
Muhammad
Sani Umar
Rijiyar
Lemo
FAYYAT
ACCE
N BAY
ANI
MA 'ANONI D
NA
A SHIRI
YAR AL
KUR'A
NI
البيان
القرآن
أوضح
لمعاني
وهدايات
(باللغة الهوسا)
6
5
4
3
2
1
بينات


FAYYATACCEN BAYANI
NA
MA'ANONI DA SHIRIYAR ALKUR'ANI
أَوْضَحُ الْبَيَانِ
لِمَعَانِي وَهِدَايَاتِ الْقُرْآنِ
(بِاللُّغَةِ الْهَوسَا)
Na
Muhammad Sani Umar Rijiyar Lemo
Sashin Shari'a Da Nazarin Addinin Musulunci
Jami'ar Bayero Kano, Najeriya
Na Shida

FAYYATACCEN BAYANI NA MA’ANONI DA SHIRIYAR AL KUR’ANI

أَوْصَحُ الْبَيَانْ لِمَعَانِيى وَهَدَايَاتِ الْقُرْآنِ

(بِاللُّغَةِ الْهَوْسَا)

Na

Muhammad Sani Umar Rijiyar Lemo

Sashin Shari’a Da Nazarin Addinin Musulunci

Jami’ar bayero Kano, Nigeria

Waɗanda suka yi bita

Farfesa Muhammad Kabir Yunus

Sashin Nazarin Addininmusulunci

Jami’ar jahar Gombe Najeria

Ferfesa Bello Sa’id

Cibiyar Nazarin Harsunan Najeriya da Fassara

Da Hikimomin Al’umma

Jami’ar Bayero Kano, Najeriya

001. Suratul Fatiha

Mabuɗin sura:

1.Sunanta:
Ana kiran wannan Sura da suna *'Fatihatul Kitab'*, kamar yadda ya zo cikin hadisin Ubadatu ɗan Samit (Allah ya kara masa yarda) [Dubi, Bukhari #756 da Muslim #394], saboda ita ce Sura ta farkon a cikin Alƙur'ani.
Hakanan ana kiran ta da sunaye kamar: *Ummul Kur'an* [Dubi, Bukhari #772, da Muslim #772]. Ana kiran ta Ummul Kitab da Sab'ul Mathani, kamar yadda ya zo a cikin hadisin Abu Huraira [Abu Dawud #1457 da Tirmizi #3124].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
An saukar da ita a Makka bisa ga ra'ayin da dama daga cikin malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta biyar (5) a jerin saukar surorin Alƙur'ani.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta bakwai ne (7), bisa ga ra'ayin mafiya yawan malamai.

5. **Falalarta**:
Hadisai sun zo da bayanin falalar karanta ta:
• Dole ne mutum ya karanta ta a cikin sallolinsa, idan bai karanta ta ba to ba shi da salla. [Dubi, Bukhari #756 da Muslim #394].
• Ita ce mafi girman Sura da aka saukar a cikin Alƙur'ani da Attaura da Injila. [Dubi, Bukhari #4474].
• Ita ce surar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya raba ayoyinta tsakaninsa da bawansa mai karanta ta, kamar yadda ya zo cikin hadisin Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda). [Muslim #395].
• Ita ce ruƙya da ake karanta ta don neman waraka daga wata rashin lafiya, kamar yadda ya zo cikin hadisin Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya kara masa yarda). [Bukhari #5007 da Muslim #2201].

6. Babban Jigonta:
Tabbatar da wajabcin fuskantar da bauta ga Allah shi kaɗai.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Surar ta ƙunshi ishara zuwa ga abin da Alƙur'ani ya ƙunsa na bayanin kaɗaitar Allah Ta'ala da siffofinsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai.
• Kamar yadda ta ƙunshi ishara zuwa ga tabbatar da tashin alƙiyama wanda Allah zai yi hisabi a cikinsa ya saka wa kowa gwargwadon aikinsa.
• Kamar yadda ta nuna karkasuwar mutane zuwa gida uku: Kaso na farko su ne waɗanda suka san gaskiya kuma suka yi aiki da ita. Waɗannan su ne masu samun babban rabo. Sai kaso na biyu, waɗanda suka san gaskiya sannan suka bijire mata. Waɗannan su ne waɗanda Allah ya yi fushi da su. Sai kaso na uku, su ne waɗanda suke aikin ɓata cikin jahilci da ɗimuwa. Waɗannan su ne ɓatattu.

• Surar tana yin ishara da wannan ne zuwa ga abin da Alƙur'ani ya ƙunsa na tarihin al'ummomi da kashe-kashensu.

Suratul Fatiha (1)

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ١

1. Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

Malamai sun haɗu a kan cewa, Bisimilla Alƙur'ani ce, kuma aya ce a cikin ‘Suratun Namli’; sai dai sun saba a kan cewa, shin aya ce a farkon kowace sura ko a'a? Zance dai mafi rinjaye shi ne ita aya ce a farkon ‘Suratul Fatiha’, sannan an saukar da ita a farkon kowace sura don bambance tsakanin ƙarshen sura da farkon wata sura. Amma ban da tsakanin ‘Suratul Anfal’ da ‘Tauba'.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Alƙur’ani da ambaton sunansa Allah, wato sunan da ya cancanta a bauta masa shi kaɗai da shi, saboda ya siffantu da siffofin kamala. Daga cikinsu akwai siffofinsa kuma sunayensa: Arrahman wanda yake nuna yalwatacciyar rahmar Allah wadda take shafar kowa da komai a nan duniya da kuma sunansa Arrahim, wanda suke nuna keɓantacciyar rahamarsa a lahira ga muminai kawai masu tsoran sa. Don haka wajibi ne mumini ya tabbatar wa Allah dukkan sunayensa da siffofinsa kamar yadda suka zo a Alƙur'ani da sunnar Annabi (ﷺ) ba tare da canza musu ma'ana ba, ko kamanta su da siffofin halittarsa ba.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yabo ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma shi ne ya cancanci yabo tun kafin ya yi haliccin halitunsa duka, saboda maɗaukakan siffofi da ya siffantu da su.

2. Tabbatar da Ɗayantakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ta hanyar tabbatar da keɓantakarsa da cancantar yabo wanda babu wani da ya yi tarayya da shi a cikinsa.

3. Tabbatar da Rububiyyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga kowa da komai.

4. Gabatar da siffarsa ta Uluhiyya a kan siffarsa ta Rububiyya domin nuna muhimmanci wannan nau'i na Tauhidi.

5. Tarbiyyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta musamman ga annabawansa da waliyyansa ta hanyar shiryar da su da koyar da su da nuna musu abin da yake shi ne maslaha ga rayuwarsu ta duniya da ta lahira. Da kuma shiryarwarsa ta bai ɗaya ga dukkan halittarsa.

Suratul Fatiha (2)

ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢

2. Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

Duk wata siffa ta yabo da kirari ta tabbata ga Allah shi kaɗai. Shi ne Ubangijin ɗaukacin talikai mahaliccinsu wanda yake renon su da ni'imominsa. Renon Allah ga halittarsa iri biyu ne: Na ɗaya, ya shafi kowa da komai, wanda ya haɗa da halittarsa da bayar da arziki da nuna wa halittunsa abin da yake maslaha gare su. Na biyu, renonsa ga muminai waɗanda suka amsa kiran annabawansa, watau datar da

su wajen karɓar shiriya da gaskiya da kuma aiki da ita. Wannan reno ne da tarbiyya da ta keɓanci annabawa da mabiyansu kaɗai.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cikakken mulki ranar alƙiyama.

2. Yana daga cikin abin da ya sanya ya cancanci yabo marar iyaka mulkinsa na ranar alƙiyama, a ranar zai tashi duk halittunsa baki ɗaya har dabbobi da tsitsaye, ya yi musu hisabi, ya ba wa kowa haƙƙinsa. Wannan kuwa ita ce ranar sakamako na adalci.

3. Tunatar da bayinsa ranar alƙiyama, Sdomin kowa ya tashi ya yi kyakkyawan aikin da zai tserar da shi daga azabar wannan rana.

4. Bayanin ranar gushewar mulkin duk wani mai mulki sai na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kaɗai.

Suratul Fatiha (3-4)

ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ٣ مَٰلِكِ يَوۡمِ ٱلدِّينِ ٤

3. Mai rahama Mai jin ƙai.

4.Mamallakin ranar sakamako.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai mulki na haƙiƙa, wanda yake sawa a yi kuma ya hana, yake kuma ba da sakamako kyakkyawa da mummuna, yake yin abin da ya ga dama a masarautarsa wadda ta haɗe sama da ƙasa da duk abin da yake tsakaninsu. Hakanan shi ne mai mulki ranar alƙiyama yayin da zai yi wa kowa hisabi bisa ga ayyukansa na ƙwarai ko mummuna. A ranar kowa zai tabbatar da cewa, Allah shi ne Ɗaya mai cikakken iko, yayin da zai ga sarakuna da talakawasu da masu kuɗi da matalauta da iyayen giji da bayinsu, duk sun daidaita a gaban mai mulki Ɗaya shi ne Allah, wanda babu mai ja da shi a wannan ranar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin tsantsanta bauta ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da kuma neman cikakken taimako wajensa shi kaɗai.

2. Nisantar shirka kowace iri ce.

3. Bawa ya dogara ga Allah shi kaɗai ya nemi taikmakonsa a kan dukkan al'amurarsa. Hatta bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba za ta yiwu ba ga bawa har sai Allah ya dafa masa.

Suratul Fatiha (5)

إِيَّاكَ نَعۡبُدُ وَإِيَّاكَ نَسۡتَعِينُ ٥

5. Kai kaɗai muke bautata wa, kuma Kai kaɗai muke neman taimakonka.

Watau Allah kaɗai muka yarda mu bauta wa; dukkan nau'o'in ibada gare shi ake ba da su. Ibada kuwa ita ce, duk wani abu da Allah yake son sa kuma ya yarda da shi, na ƙuduri ne a zuciya ko magana ta baka ko kuma aiki na gaɓobi. Sannan mun tabbata ba za mu iya bauta masa yadda ya dace ba sai da taimakonsa. Don haka a wajensa kaɗai muke neman taimako a cikin lamuranmu gaba ɗaya. Wannan yana nuna ba a neman taimakon wani wanda ba Allah ba a duk wani abu da Allah ne kaɗai zai iya yin sa, kamar bayar da arziki ko neman lafiya ko neman 'ya'ya da makamantansu. Bai halatta wani ya kira wani annabi ko wani waliyyi ko wani salihin bawa ba yayin da yake cikin wata musiba don ya taimake shi, idan har ya yi haka to ya bayar da haƙƙin Allah ga wani, watau ya yi shirka da Allah.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babban abin da bawa yake buƙata a wajen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne ya shiryar da shi bin tafarkin gaskiya da riko da shari'arsa.

2. Gargaɗi game da bin hanyoyi bid'a da sauran gurɓatattun hanyoyi.

3. Tabbatar da annabta, domin ba za a iya gane tafarki madaidaici ba sai ta hanyar wahayi daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Fatiha (6)

ٱهۡدِنَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلۡمُسۡتَقِيمَ ٦

6. Ka shiryar da mu tafarkin nan madaidaici.

Muna roƙon Allah ya nuna mana hanaya miƙaƙƙiya wadda za ta kai mu ga samun yardarsa da rahamarsa, watau sanin gaskiya da aiki da ita da kama addinin Musulunci da barin duk wani addini da ba shi ba. Wannan addu'a ce mai matuƙar amfani ga rayuwar bawa mumini; shi ya sa Allah ya shar'anta mana karanta *Fatiha* a cikin kowace raka'a a sallolinmu na farilla da na nafila.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cewa aƙidar muminai guda ɗaya ce, ba wasu hanyoyi ne mabanbanta ba.

2. Jahilci da taurin kai suna daga cikin abubuwan da suke jawo kauce wa tafarki madaidaici.

3. Kafircin Yahudawa ya ɗara kafircin Nasara, saboda su Yahudawa sun san gaskiya suka take ta, suke kuma yakar ta. Amma su Nasara jahilci ne ya sa suke gaba da gaskiya.

4. Tabbatar da cewa hanyar mabiya gaskiya ita ce yin ilimi da aiki da shi.

5. Bayanin cewa ni'imar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tana tare da waɗanda suka bi tafarkinsa ne kawai ba waɗanda suka kauce masa ba.

6. Ɗebe wa mabiya gaskiya kewarsu a koyaushe musamman yayin da suke tsakiyar gurɓatattun mutane, don su gane cewa hanyar da suke kai ba su kaɗai ne suke bin ta ba, duk annabawa da salihai da suka gabata a kanta suke, don haka wannan zai ƙara musu ƙarfin gwiwa da tsayawa a kan tafarkin gaskiya.

7. Mayar da martani ga masu kiraye-kiraye a kan haɗa addinai wuri guda, domin babu yadda zai yiwu mabiya gaskiya su haɗa hanyar addini da waɗanda Allah ya yi hushi da su ya la'ance su ba.

8. Duk malamain da ya san gaskiya ya take ta, to ya bi hanyar Yahudawa ne. Duk kuma mai ibadar da ya bauta wa Allah da jahilci, to ya bi hanyar Nasara ne.

Suratul Fatiha (7)

صِرَٰطَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمۡتَ عَلَيۡهِمۡ غَيۡرِ ٱلۡمَغۡضُوبِ عَلَيۡهِمۡ وَلَا ٱلضَّآلِّينَ ٧

7. Tafarkin waɗanda Ka yi wa ni'ima, ba waɗanda aka yi fushi da su ba, ba kuma ɓatattu ba.

Miƙaƙƙen tafarki shi ne tafarkin annabawa da siddiƙai da shahidai da salihan bayi, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata hakan a *Suratun Nisa'i*' aya ta 69. Su ne waɗanda Allah ya yi musu katari da ni'imar shiriya a duniya, don haka suka cancanci ni'imar lahira. Hanyar waɗannan bayin Allah kuwa ta yi hannun riga da hanyar waɗanda suka san gaskiya amma suka take ta, suka koma ga bin soye-soyen zukatansu, kamar Yahudawa. Hakanan ta yi hannun riga da hanyar waɗanda suke bautar Allah da jahilci da ɓata, kamar Nasara.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman mu'ujizar Alƙur'ani.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi ishara zuwa ga cewa, za a tattara Alƙur'ni wuri guda don ya zama littafin da Musulmi za su riƙa ɗauka suna karantawa a kowane zamani.

3. Alƙur'ani shiriya ne ga mutune masu taƙawa, watau masu kiyaye dokokin Allah. Gwardon taƙawar bawa gwargwadon yadda zai dace da shiriyar Alƙur'ani. Wanda kuma ya rungume shi yana aiki da shi to babu shakka shiriyarsa za ta riƙa hauhawa tana ƙaruwa.

4. Duk abin da Alƙur'ani ya ƙunsa gaskiya ne babu kokwanto ko kaɗan a cikinsa.

5. Falalar yin imani da gaibu, domin shi ne abin da yake buƙatar ƙarfin imani, saɓanin abin da kowa yake iya gani ko yake iya ji, wannan abu ne da babu mai iya musunta samuwarsa.

6. Girman sha'anin tsai da salla, domin ita ce rukuni na biyu daga cikin rukunan Musulunci.

7. Falalar ciyar da dukiya don Allah.

8. Siffar masu taƙawa ta ƙunshi bauta wa mahalicci da kyautata wa mahaluki.

9. Imani da duk littattafan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa manzanninsa, domin sanin cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai bar bayinsa hakanan sakaka ba tare da bayyana musu hanyar shiriya ba.

10. Shiriya da rabauta ba za su taɓa samuwa ga bawa ba har sai ya rungumi wannan hanyar, ya kuma siffantu da waɗannan siffofi.

2-Suratul Baƙara

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da wannan suna saboda labarin saniya da ya zo a cikinta, babu inda aka sake ba da labarinta a cikin Alƙur'ani.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Wannan Sura *Madaniyya* ce, watau an saukar da ita ne bayan Annabi (ﷺ) ya yi hijira zuwa Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin da bakwai (87) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *'Suratut Tadfifi*' gabanin *'Suratu Ali-Imarana'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta a lissafin mutanen Kufa ɗari biyu da tamanin da shida ne (286). A lissafin mutanen Madina da Makka da Sham kuwa adadinsu ɗari biyu da tamanin da biyar ne (285). A wurin mutanen Basra kuwa ɗari biyu da tamanin da bakwai ne (287).

5. Falalarta:
Hakim ya ruwaito [Mustadrak 1:748] daga Abdullahi ɗan Mas'ud ya ce: "Kowane abu yana da tozo, kuma tozon Alƙur'ani shi ne *Suratul Baƙara'*. Kuma Shaiɗan idan ya ji ana karanta *Suratul Baƙara*' a cikin gida sai ya fice daga gidan." [Dubi, Al-Albani, *As-Sahihah* #588].

Bukhari [#5018] da Muslim [#796] kuma sun ruwaito hadisi daga Usaid bn Hudhair (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Ya Manzon Allah, jiya da daddare ina karanta *Suratul Baƙara* sai na ji wata ƙarar faɗuwar wani abu a bayana, sai na yi tsammani ko dokina ne ya tsinke. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ci gaba da karatunka ya baban Atiku." Ya ce: Sai na waiwaya sai na ga kamar wata fitila ce take reto tsakanin sama da ƙasa. Manzon Allah kuwa ya ci gaba da faɗa masa: "Yi karatunka ya Baban Atiku." Ya ce: Ya Manzo Allah, ai ban iya ci gaba da karatun nan ba. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ai waɗannan mala'iku ne waɗanda suka sauko don sauraron karatun *Suratul Baƙara*. Da a ce ka ci gaba da karatun da ka ga abubuwan mamaki."

Muslim [#804] ya ruwaito daga Abu Umamatal Bahili (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Ku karanta Alƙur'ani domin zai zo ranar alƙiyama yana mai ceton makarantansa. Ku karanta masu haske guda biyu, *Baƙara* da *Suratu Ali Imran*, za su zo ranar alƙiyama kamar wasu gizagizai guda biyu, ko kamar wasu ƙungiyoyi biyu na tsuntsaye masu tafiya sahu-sahu, suna jayayya don kare makarantansu. Ku karanta *Suratul Baƙara*, domin koyon ta albarka ne, barin ta kuma nadama ce, matsafa ba za su iya da ita ba."

Muslim [#780] ya ruwaito hadisi daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kada ku mayar da gidajenku kamar maƙabartu. Ku riƙa yin salla a cikinsu. Shaiɗan yana guje wa gidan da ya ji ana karanta *Suratul Baƙara* a cikinsa.”

6. Babbar Jigonta:
Samar da al'ummar da za ta raya bayan ƙasa da bautar Allah da riƙo da addininsa. Ta yi bayanin rarrabuwar mutane da siffofi kowane rukuni nasu, tare da bayin ginshiƙan shari'a da manya-manyan hukunce-hukuncenta.

7. Daga Cikin abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
Kasancewar wannan Sura ta sauka a lokacin da ake kafa daular Musulunci ta farko a Madina, sai ta fi ba da ƙarfi wajen kafa tarbiyyar zamantakewa tsakanin al'umma da ƙoƙarin tace ta daga dukkan wasu gurɓattattun mutane waɗanda suke ɓarna da sunan gyara. Don haka Surar ta koyar da hukunce-hukunce da dama waɗanda suka shafi rayuwar al'umma, tare da bayanin ni'imomin da Allah ya yi wa ‘yan’adam tun sanda Allah ya halicci Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ya ba shi ɗaukaka ya hore masa abin da yake sama da ƙasa domin amfaninsa, tare da tunatar da shi ƙiyayyar Shaiɗan da mabiyansa a kowane zamani, waɗanda suka zaɓi su kafirce wa hanyar Allah da bin hanyar Shaiɗan, kamar Yahudu da Nasara da mushirikai.
Cikin irin waɗannan hukunce-hukunce Allah ya bayyana hukuncin ƙisasi da wasiyya da na azumi da i'itikafi da Hajji da jihadi da tsarin zamantakewar iyali da mu'amalar kuɗi da rantsuwa da sadaka da hukuncin kayan maye da hukuncin marayu da na gado da ciniki da riba da bashi da aure da hukunce-hukuncen da suka shafi mata kamar idda da saki da shayarwa da ciyarwa, da sauransu.

Suratul Baƙara (1-5)
الٓمٓ ۝١ ذَٰلِكَ ٱلۡكِتَٰبُ لَا رَيۡبَۛ فِيهِۛ هُدٗى لِّلۡمُتَّقِينَ ۝٢ ٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡغَيۡبِ وَيُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ۝٣ وَٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبۡلِكَ وَبِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ يُوقِنُونَ ۝٤ أُوْلَٰٓئِكَ عَلَىٰ هُدٗى مِّن رَّبِّهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1.Alif Lam Mim.

2. Wannan littafi ne da babu wani kokwanto a cikinsa; shiriya ne ga masu taƙawa.

3. Waɗanda suke yin imani da gaibi kuma suke tsayar da salla kuma suke ciyarwa daga abin da Muka azurta su da shi.

4. Waɗanda suke yin imani da abin da aka saukar maka da abin da aka saukar a gabaninka, kuma suke sakankancewa da ranar lahira.

5. Waɗannan suna kan (babbar) shiriya daga Ubangijinsu, kuma waɗannan su ne masu samun babban rabo.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da harufin ***Alif da Lam*** da ***Mim***. Ban da ita wannan Sura da akwai surorin Alƙur'ani da dama da Allah ya buɗe su da irin waɗannan haruffa. Da dama daga cikin malamai suna cewa, Allah ne kaɗai ya san abin da yake nufi da su. Wasu kuma sun yi ƙoƙarin bayyan ma’anonisu. Amma magana mafi inganci ita ce, Allah yana nuna mu'ujizar Alƙurani ne ta hanyar

ambaton waɗannan haruffa. Domin suna tabbatar wa larabawa cewa babu wanda zai iya kawo wani abu irin Alƙur'ani, duk kuwa da cewa haruffansa su ne haruffan da suke magana da rubutu da su.

Allah ya siffanta wannan Alƙur'ani da cewa, babu wani kokwanto a cikinsa, wato duk abin da ya ƙunsa tabbatace ne kuma gaskiya ne, don haka ne ya zama shiriya ga masu taƙawa, yana nuna musu gaskiya da bayyana musu hukunce-hukunce waɗanda suka shafi aƙidunsu da ibadunsu da kuma mu'amalolinsu.
An kira Alƙur'ani da sunan *Littafi* duk kuwa da kasancewarsa a lokacin ba a tattara shi wuri guda ba; an yi haka ne domin a yi ishara zuwa ga cewa, nan gaba za a tattara shi wuri guda ya zama littafi wanda Musulmi a kowane lokaci za su riƙa karantawa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fayyace siffofin masu taƙawa waɗanda Alƙur'ani yake shiryar da su. Sun siffantu da siffofi guda biyar kamar haka:
Siffa ta farko: Suna yin imani da gaibu. Gaibu shi ne duk abin da manzanni suka zo da shi, suka ba da labarinsa, kuma ido bai gan shi ba, wani tunani bai riske shi ba. Wannan ya haɗa da imani da ranar lahira da abin da ta ƙunsa na hisabi da mala'iku da labarin manzanni da littafan da Allah ya saukar gabanin zuwan Manzon Allah (ﷺ). Imani da gaibu shi ne yake bambance wa tsakanin mutum mumini da kafiri, saboda yana imani da duk wani abu da Allah ya ba da labarinsa ko Manzonsa ya faɗa ko da kuwa bai gano shi da hankalinsa ba.
Siffa ta biyu: Suna tsayar da salla, wato suna yin ta kamar yadda shari'a ta koyar da su tare da kula da lokutanta da rukunanta da wajibanta da sharuɗɗanta.
Siffa ta uku: Suna ciyar da abin da Allah ya arzuta su da shi. Sukan fitar da zakkar dukiyoyinsu, hakanan suna sadaka ta nafila da abin da Allah ya hore musu.
Siffa ta huɗu: Su ne waɗanda suke yin imani da Alƙur'anin da Allah ya saukar wa Annabi Muhammadu (ﷺ) gaba ɗaya ba tare da ware wani ɓangare ko su riƙa karkatar da ma'anonin wani ɓangare nasa ba, kamar yadda 'yan bidi'a suke yi ga wasu ayoyin waɗanda ba sa goyon bayan bidi'o'insu da aƙidunsu. Hakanan suna yin imani da dukkan littattafan da Allah ya saukar wa manzanni da annabawan da suka gabata, har da su kansu manzannin da annabawan.
Siffa ta biyar: Su ne waɗanda suka tabbatar da zuwan ranar tashin alƙiyama da abubuwan da za ta zo da su na tayar da matattu da yi musu hisabi da saka wa mutanen ƙwarai da Aljanna; masu miyagun laifuffuka kuwa a saka musu da wutar Jahannama. An ware batun imani da ranar lahira duk kuwa da cewa ya shiga cikin batun imani da gaibu, saboda a zaburar da mutane ga ayyukan alheri a kuma tsoratar da su game da munanan ayyuka.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗi sakamakon masu waɗannan siffofi da cewa, suna kan wata shiriya mai girma daga Allah mai yi musu tarbiya ta ƙwarai. Domin babu wata shiriya da ta kai siffantuwa da waɗannan siffofi. Don haka su ne waɗannan suke da babban rabo daga Allah, wato samun yardar Allah da gidan Aljanna ranar gobe alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin Annabi (ﷺ) da nuna masa kada damuwa ta hallaka shi saboda ganin mutanensa sun ƙi yin imani da gaskiyar da yake kiran su zuwa gare ta.

2. Idan mai kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutane gaskiya suka bijre masa, to wannan ba zai cutar da shi komai ba, domin shi ya sauke nayin da yake kansa.

3. Annabi ko waninsa babu wanda ya san abin da Allah ya riga ya rubuta wa waɗanda ake kira na shiryuwarsu ko ɓatansu, Allah ne kaɗai ya san haka.

4. Tsananin haɗarin girman kai da bijire wa gaskiya da dogewa a kan kafirci, domin yin haka yakan toshe zukata har ya zamanto duk wani alheri ba ya ratsa su.

Suratul Baƙara (6-7)

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ سَوَآءٌ عَلَيۡهِمۡ ءَأَنذَرۡتَهُمۡ أَمۡ لَمۡ تُنذِرۡهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ٦ خَتَمَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ وَعَلَىٰ سَمۡعِهِمۡۖ وَعَلَىٰٓ أَبۡصَٰرِهِمۡ غِشَٰوَةٞۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ٧

6. Lalle waɗanda suka kafirta, duk ɗaya ne a gare su, ka yi musu gargaɗi ko ba ka yi musu ba, ba za su yi imani ba.

7. Allah Ya toshe zukatansu da jinsu, kuma akwai wani lulluɓi a kan idanunsu, kuma suna da azaba mai girma.

A nan Allah yana ba da labarin kafirai ne da irin taurin kansu wajen kafirce wa abin da Annabi (ﷺ) ya zo da shi na gaskiya. Allah ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, waɗannan kafirai sun kai matuƙa ga kafircinsu; yana da wuya wa'azinsa ya sa su saurare shi, har su yi imani, don haka kada kafircinsu ya dame shi. Domin Allah ya riga ya toshe musu zukatansu saboda zunubbansu, don haka imani ba zai sami hanyar shiga cikinsu ba. Kuma ya doƈe musu kunnuwansu saboda kafircinsu, don haka ba za su taɓa jin kiransa ba balle su amsa masa. Sannan akwai yanar da ta rufe musu idanuwansu ta yadda ba za su taɓa ganin gaskiya ba balle su yarda da ita. Saboda haka suka cancanci azaba mai girman gaske. Wannan yana nuna cewa, kafirci idan ya yi yawa a tare da bawa yakan toshe masa dukkan ƙofofin samun shiriya, duk kuwa yadda aka yi fama da shi ba zai taɓa karɓar gaskiya ba, don ba ya jin ta ba ya ganin ta kuma ba ya fahimtar ta saboda tsatsar zunubi da kafirci da suka lulluɓe shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka

1. Faɗakarwa a kan haɗarin munafurci da munafukai.

2. Furta kalmar shahada da baki kawai ba zai wadatar ba har sai zuciya ta ƙudurce ta, domin Musulunci na gaskiya shi ne miƙa wuya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a zahiri da baɗini.

3. Munafukai suna nuna wa Musulmi cewa sun yi imani, alhalin ƙarya suke yi ba su yi imani ba.

4. Luɗufin da Allah ya yi wa muminai yayin da ya tona asirin munafukai tun da wuri.

5. Tabbatar da cewa munafukai ba muminai ba ne samsam.

6. Munafukai mayaudara ne, don haka wajibi ne ga muminai su yi hattara da su.

7. Duk yaudarar mayaudari a kansa za ta ƙare.

8. Munafurci yana toshe basira, don haka duk wani munafuki ba ya fahimatar cewa kansa yake cuta.

9. Munafurci muguwar cuta ce wadda idan mai ita bai yi saurin magance ta ba, to za ta yi ta ƙaruwa ne har ta kai shi ga aukawa cikin azaba mai raɗaɗi.

10. Haɗarin ƙarya da ƙaryata gaskiya. Karya a wurin munafiki ƙaruwa take yi koyaushe.

Suratul Baƙara (8-10)

وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَقُولُ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَبِٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَمَا هُم بِمُؤۡمِنِينَ ٨ يُخَٰدِعُونَ ٱللَّهَ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَمَا يَخۡدَعُونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمۡ وَمَا يَشۡعُرُونَ ٩ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ فَزَادَهُمُ ٱللَّهُ مَرَضٗاۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمُۢ بِمَا كَانُواْ يَكۡذِبُونَ ١٠

8. A cikin mutane kuma akwai waɗanda suke cewa: “Mun yi imani da Allah kuma mun yi imani da ranar lahira,” alhalin su ba muminai ne ba.

9. Suna ganin suna yaudarar Allah ne da waɗanda suka yi imani, amma kuwa ba kowa suke yaudara ba sai kawunansu, kuma su ba sa jin hakan.

10. Akwai wata cuta (ta munafunci) a cikin zukatansu, sai Allah Ya ƙara musu wata cutar, kuma suna da wata azaba mai raɗaɗi saboda ƙaryar da suke yi.

Daga nan har zuwa aya ta 20 Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana mana bayanin munafuƙai ne tare da fallasa su da bankaɗo munanan siffofinsu don kowa ya gane su a kowane lokaci a kuma kowane yanayi. A lokacin da Annabi (ﷺ) yana zaune a Makka mutane kashi biyu ne: muminai sai kafirai. To amma bayan Musulmai sun yi hijira zuwa Madina, sai aka samu kashi na uku, su ne munafuƙai. Munafiki shi ne wanda yake bayyana Musulunci a bakinsa, amma yana ɓoye kafirci a zuciyarsa. Allah ya bayyana wasu siffofinsu a nan.
Yana daga cikin siffofinsu suka riƙa bayyana imani da baki amma suna ɓoye kafirci a zukatansu, shi ya sa Allah ya ce: “Waɗannan ba muminai ne ba.” Kuma saboda wautarsu suna yin haka ne wai don a zatonsu suna yaudarar Allah ne tare da muminai, watau a tsammaninsu Allah bai san abin da suke ɓoyewa ba. Wannan ta sa idan yaƙi ya ɓarke tsakanin muminai da kafirai to su ba za a taɓa su ba, kuma ba za a taɓa dukiyarsu ba, sannan in an ci nasara a kan kafirai aka samo ganima, to tare da su za a raba. To amma ba su san cewa, kawunansu kaɗai suke yaudara ba, domin babu mai cutuwa da abin da suke yi sai su kaɗai. Allah ya ce, akwai cuta a zukatansu. Cutar kuwa ita ce ta shakka da ruɗani da munafunci, wannan ya sanya Allah ya ƙara musu wata cutar, domin duk sanda aka saukar da wata aya ga Annabi (ﷺ) to za su kafirce mata, sai cutar zukatansu ta ƙara hauhawa, haka za su yi ta rayuwa har mutuwarsu sannan su je su tarar da azaba mai raɗaɗi tana jiran su a lahira saboda ƙaryar da suke ƙirƙira da kuma ƙaryata Annabi (ﷺ) da suka riƙa yi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: “Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: “Alamar munafiƙi uku ce: Idan ya yi magana sai ya yi ƙarya, kuma idan ya yi alƙawari sai ya saɓa, idan kuma aka amince masa sai ya yi ha’inci.” [Bukhari #33 da Muslim #59].

Daga waɗannan ayoyin za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Munafurci babbar ɓarna ce a bayan ƙasa.

2. Yana daga cikin babban bala'i ga mutum a ƙawata masa mummunan aikinsa har ya riƙa ganinsa kyakkyawa.

3. Haɗarin dake tattare da rikirkicewar tunani wanda zai kai ga maɓarnaci ya riƙa ɗaukan kansa wai shi mai gyara ne.

4. Daga cikin mummunar siyasar munafukai a kowane zamani shi ne yadda suke sanya rigar masu kawo gyara cikin al'umma, masu fafutukar daidata rayuwar jama'a, amma a fakaice suna yaƙi da addini da masu addini, suna yi wa abokan gabar Musulmi farfaganda domin lalata aƙidun Musulmi da kyawawan halayensu na addini da zamantakewa da shugabanci.

5. Faɗakar da muminai da jawo hankalinsu a kan kada su ruɗu da da'awar munafukai da yaudararsu.

6. Kiran munafukai zuwa ga abin alheri sau tari ba shi da wani amfani, domin yadda suke taƙama da ɓarnar da suke kai yana ƙara musu bijire wa gaskiya.

7. Kariyar da Allah yake ba wa sahabban Annabi ﷺ da muminai.

8. Tabbatar da jahilcin munafukai.

9. Duk maɓarnacin da ba ya gane cewa shi maɓarnaci ne, to shi wawa ne.

Suratul Baƙara (11-13)

وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ لَا تُفْسِدُواْ فِي ٱلْأَرْضِ قَالُوٓاْ إِنَّمَا نَحْنُ مُصْلِحُونَ ۝١١ أَلَآ إِنَّهُمْ هُمُ ٱلْمُفْسِدُونَ وَلَٰكِن لَّا يَشْعُرُونَ ۝١٢ وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ ءَامِنُواْ كَمَآ ءَامَنَ ٱلنَّاسُ قَالُوٓاْ أَنُؤْمِنُ كَمَآ ءَامَنَ ٱلسُّفَهَآءُ ۗ أَلَآ إِنَّهُمْ هُمُ ٱلسُّفَهَآءُ وَلَٰكِن لَّا يَعْلَمُونَ ۝١٣

11. Idan kuma aka ce musu: “Kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa”, sai su ce: “Mu fa masu gyara ne kawai.”

12. Saurara, lalle su su ne maɓarnata, amma ba sa jin hakan.

13. Idan kuma aka ce da su: “Ku yi imani kamar yadda mutane suka yi imani”, sai su ce: “Shin za mu yi imani ne kamar yadda wawaye suka yi imani?” Saurara, lalle su ne wawayen, sai dai ba sanin (hakan).

Har ila yau, Allah yana ƙara bayyana wani mugun halin na munafuƙai wanda shi ne, duk sa’adda sahabbai za su yi musu wa’azi su nuna musu kuskurensu, su neme su da su tuba zuwa ga Allah, sai su riƙa yi wa sahabban kallon wasu wawaye jahilai marasa hankali da har suka yarda suka bar garuruwansu da gidajensu da dukiyoyinsu suka yi hijira don wai su yi addinin Musulunci; sai su nuna su fa ba za su taba yin wauta irin wannan ba. Sai Allah ya mayar musu da martani da cewa, ai ko su ne tsantsar wawaye, tun da har suka guje wa abin da zai amfane su na imani da Allah suka rungumi abin da zai cutar da su saboda tsabar jahilci da wauta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kasƙancin munafukai da wulaƙanta kansu da suke yi da kuma nuna son duniya shi ne ya haifar musu da munafurci a zukatansu.

2. Duk wanda zai riƙa nuna fuska-biyu ya kuma riƙa ɓoye rashin gaskiyarsa, to wannan ƙasƙantaccen mutum ne.

3. Bayyana yadda munafukai suke haɗa kai da kafirai maƙiya Musulunci domin yaƙar Musulmi.

4. Damuwar munafukai har kullum ita ce, yadda za su gamsar da 'yan'uwansu kafirai cewa, manufarsu guda ɗaya ce, kuma su fa imaninsu ba na gaskiya ne ba.

5. Bayanin yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake kunyata munafukai, yake fallasa abin da suke faɗa wa kafurai a asirce.

6. Haɗarin yi wa muminai izgili, domin yin haka siffa ce ta munafukai.7. Irin aikin mutum irin sakamakonsu, yadda munafukai suke yi wa muminai izgili su ma haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake saka musu da yi musu izgli.

Suratul Baƙara (14-15)

وَإِذَا لَقُواْ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَوۡاْ إِلَىٰ شَيَٰطِينِهِمۡ قَالُوٓاْ إِنَّا مَعَكُمۡ إِنَّمَا نَحۡنُ مُسۡتَهۡزِءُونَ١٤ ٱللَّهُ يَسۡتَهۡزِئُ بِهِمۡ وَيَمُدُّهُمۡ فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ١٥

14. Idan kuma suka haɗu da waɗanda suka yi imani sai su ce: “Mun yi imani.” To amma idan suka keɓanta da shaiɗanunsu (iyayen gidansu) sai su ce: “Mu fa lalle muna nan tare da ku, mu kwai izgili ne muke yi.”

15. Allah Yana yi musu izgili, kuma Yana yi musu talala cikin shisshiginsu suna masu ɗimuwa.
Wata muguwar sifa ta munafuƙai kuma har ila yau ita ce, yin fuska-biyu, wato idan sun shiga cikin muminai ko sun haɗu da su a hanya sai su riƙa nuna musu suna tare da su, su ma wai muminai ne. To amma da zarar sun koma ga manyan kafirai ko Yahudawa sai su nuna musu cewa, mu fa tare da ku muke, ku bar waɗancan muminai izgili kawai muke yi musu, amma zuciyarmu ba ta son su ko kaɗan. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa: Ai Allah ne yake yin izgili gare su, shi ya sa ya ƙyale su ba tare da ya ba wa muminai ɗama su gama da su ba, yake kuma ƙawata musu munanan ayyukansu, har ma suke zaton ko a kan gaskiya suke, ba su san cikin ɗimuwa da duhu suke rayuwa ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayani game da tsantsar wautar munafukai da rashin basirarsu wadda har ta kai su suke fifita ɓata a kan shiriya, domin kuwa babu wautar da ta kai irin ta wanda zai ba da kuɗi tsababa don a ba shi wata lalatacciyar kadara.

2. Duk wani attajiri yana fatan samun riba ne daga abin da zai kashe kuɗinsa ya saya. To haka su ma munafukai suna zaton cewa za su sami riba a cikin wancan lalataccen kasuwanci da suke yi, alhalin asara kawai suke tabkawa.

3. Shiriyar Allah ita ce riba ta gaske. Duk wanda yake kan shiriya ta Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) to shi ne mai samun ribar kasuwancinsa a duniya da lahira. Wanda kuwa ya rungumi ɓata kamar munafuki, to ya tabka hasara ta har abada.

4. Sau tari munafukai ba su cika shiriyuwa su dawo kan gaskiya ba.

Suratul Baƙara (16)

أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱشۡتَرَوُاْ ٱلضَّلَٰلَةَ بِٱلۡهُدَىٰ فَمَا رَبِحَت تِّجَٰرَتُهُمۡ وَمَا كَانُواْ مُهۡتَدِينَ ١٦

16. Waɗannan su ne suka musanya shiriya da ɓata, don haka kasuwancinsu bai yi riba ba, kuma ba su zamo shiryayyu ba.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana fito da haƙiƙanin matsayin munafuƙai, ta yadda suke nuna tsananin sha'awarsu da ƙaunarsu ga hanyar ɓata, suke ɗaukar ta a matsayin wata kadara mai daraja da za su iya kashe ko nawa ne don su mallake ta. Don haka suka amince su bayar da shiriya a matsayin kuɗin da za su fanshi wannan mummunar kadara (wato ɓata) da ita. Wannan shi ne haƙiƙanin kasuwancinsu a duniya; ashe kuwa wannan kasuwanci ne maras riba, kuma mai cike da hasara ta duniya da ta lahira.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Fasahar Alƙur'ani wajen buga misalai don a fahimta.

2. Munafukin da ya yi iman sannan daga baya ya yi ridda, to munafurcinsa zai gusar da alamun hasken imaninsa, don haka rayuwarsa ba ta da sauran wani amfani.

3. Munafukai sun shiga Musulunci ne saboda kwaɗayin samun ganimar duniya, don kuma su kare kansu daga kisa. To amma da zarar sun mutu duk wannan tagomashin da suke samu ya ƙare, sai azaba mai raɗaɗi ce za su haɗu da ita a ranar alƙiyama.

4. Munafukai ba sa ƙaruwa da komai na hasken wahayi da shari'a. Idan sun halarci majalisin da ake karanta shari'ar Allah, to kafircinsu da munafurcinsu ba za su ƙyale su su amafana da komai ba.

5. Sanin gaskiya ba zai yi wa bawa amfani ba idan har bai miƙa wuya ya karɓi gaskiyar ba.

6. Munafukai a duniya suna rayuwa ne ta ɗimuwa da kiɗimewa, domin suna cikin duhu ne iri-iri da zai hana su ganin gabansu.

7. Hanayar gaskiya ɗaya ce, amma hanyoyin ɓata yawa gare su.

8. Munafukai ba sa amafana da zamansu cikin mutanen kirki, domin munafurcinsu ba zai bar su su amafana da su ba.

9. Ishara zuwa ga cewa, duk wanda zai san gaskiya amma ya yi watsi da ita, to lamarinsa ya fi muni a kan wanda da ma can bai san gaskiyar ba.

10. Gaɓoɓin da Allah ya ba wa duk wani mutum don ya amfana da su, munafukai sam ba sa amfana da su.

11. Makantar zuciya da ta basira ta fi makantar ido muni. Kuma munafukai ba za su taɓa dawo wa kan gaskiya ba, domin suna ganin kyawon abin da suke aikatawa.

Suratul Baƙara (17-18)

مَثَلُهُمْ كَمَثَلِ ٱلَّذِى ٱسْتَوْقَدَ نَارًا فَلَمَّآ أَضَآءَتْ مَا حَوْلَهُۥ ذَهَبَ ٱللَّهُ بِنُورِهِمْ وَتَرَكَهُمْ فِى ظُلُمَٰتٍ لَّا يُبْصِرُونَ ﴿١٧﴾ صُمٌّۢ بُكْمٌ عُمْىٌ فَهُمْ لَا يَرْجِعُونَ ﴿١٨﴾

17. Misalinsu kamar misalin wanda ya wahala har ya kunna wuta ne, yayin da ta haskaka abin da yake daura da shi, sai Allah Ya tafiyar da haskensu Ya bar su cikin duffai ba sa gani.

18. Su kurame ne, bebaye ne, makafi ne, don haka ba za su taɓa dawowa (kan gaskiya) ba.

A nan ma Allah yana ƙara yi mana bayani ne a kan waɗannan munafuƙai, inda ya yi mana kwatance na zahiri domin mu fahimta da gaggawa; ya faɗa mana cewa, misalin halin da munafuƙai suka tsinci kansu a ciki kamar misalin wani mutum ne da yake tafiya ya samu kansa cikin matsanancin duhu, ga tsoro da ya mamaye shi ta ko'ina, sai ya yi ta fafutukar neman haske, ya wahala sosai har ya samo wuta wadda ta haskaka masa kewayansa, ya zamanto yana ganin komai da ke gabansa da bayansa, ya daina jin tsoron da yake ciki a farko, ya fara farin ciki, sai kwatsam hasken ya ɗauke, ga wuta na ci gabansa balbal, ga zafinta yana bugo shi, amma kuma babu haske sai dai duhu yana dukan duhu; ga duhun dare, ga duhun hadari, ga na ruwan sama, ga duhun rashin haske, ya samu kansa cikin duffai daban-daban ba ya ganin ko da tafin hannunsa.
haka sha'anin munafuƙai yake. Da farko suna rayuwa cikin duhun kafirci, sai Musulunci ya bayyana, sai suka ɗosani haskensa, suka sami kariya ta rayukansu da dukiyoyinsu. To amma da yake ba a kan gaskiya suka yi imani ba, sai hasken Musuluncin ya ɓace musu, yayin da suka mutu aka kai su ƙaburburansu, sai suka tsinci kansu cikin duhu na dukan duhu, ga duhun ƙabari, ga na kafirci, ga na munafunci, ga na saɓon Allah iri-iri, ga uwa-uba duhun wutar Jahannama. Tir da wannan makoma.
Dalilin haka ya sa Allah ya ce da su, su kurame ne ba sa jin duk wata gaskiya ji na fahimta; bebaye ne ba sa iya faɗin gaskiya, sannan makafi ne ba sa ganin gaskiya su bi ta. Don haka ne ma babu yadda za a yi su dawo kan hanya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoratarwa da tsawatarwa ga kafurai.

2. Yana da kyau Musulmi ya riƙa roƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jiyar da shi daɗi da jinsa da ganinsa.

3. Daga cikin mutane akwai wanda ba ya iya ginin hasken gaskiya komai karfinsa, domin zuciyarsa ba ta son gaskiya, kamar yadda ido ba ya iya jure wa kallon hasken walƙiya.

4. Hasken ilimi da imani a tare suke ga mumini, da su yake ganin hanyar binsa. Amma kafiri kuwa ba ya iya ganin hanyarsa.

5. Guje wa sauraron gaskiya ba zai kuɓutar da mutum ba, ko ya nuna rashin tsayuwar hujja a kansa.

Suratul Baƙara (19-20)

أَوۡ كَصَيِّبٖ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فِيهِ ظُلُمَٰتٞ وَرَعۡدٞ وَبَرۡقٞ يَجۡعَلُونَ أَصَٰبِعَهُمۡ فِيٓ ءَاذَانِهِم مِّنَ ٱلصَّوَٰعِقِ حَذَرَ ٱلۡمَوۡتِۚ وَٱللَّهُ مُحِيطُۢ بِٱلۡكَٰفِرِينَ ١٩ يَكَادُ ٱلۡبَرۡقُ يَخۡطَفُ أَبۡصَٰرَهُمۡۖ كُلَّمَآ أَضَآءَ لَهُم مَّشَوۡاْ فِيهِ وَإِذَآ أَظۡلَمَ عَلَيۡهِمۡ قَامُواْۚ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَذَهَبَ بِسَمۡعِهِمۡ وَأَبۡصَٰرِهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٠

19. Ko kuma (misalinsu) kamar wani mamakon ruwan sama ne, wanda yake ɗauke da duffai da tsawa da walƙiya, har ta kai suna sanya 'yan yatsunsu cikin kunnuwansu don tsananin tsawarwaki saboda tsoron mutuwa. Allah Kuma Yana kewaye da kafirai (da iliminsa).

20. Walƙiyar ta kusa ta fauce idanuwansu. Duk sa'adda ta haska musu sai su ci gaba da tafiya cikin (haskenta); idan kuma ta rufe su da duhu sai su tsaya cak. Da kuwa Allah Ya ga dama da sai Ya tafiyar da jinsu da ganinsu. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai.

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar da misali na biyu game da munafuƙai. Ya misalta su da mutanen da suke tafiya cikin ɗare sai ruwan sama ya goce kamar da bakin ƙwarya, sannan ga duhu ya baibaye su ta ko'ina; duhun ɗare da na hadari da na ruwan sama, baya ga haka ga tsawarwaki da walƙiya. Duk sa'adda walƙiya ta haska sai su ɗan motsa gaba ɗaya daga inda suke. Idan kuma duhu ya rufe su sai su tsaya cak a inda suke. Sannan idan rugugin tsawa ya dame su sai su sanya yatsunsu cikin kunnuwansu saboda tsoron halaka. Sun manta cewa ilimin Allah da Kudurarsa suna zagaye da kafirai. To kamar haka su ma munafuƙai suke, suna rayuwa cikin duhu iri-iri, suna cikin damuwa, duk sa'adda Musulmai suka samu wata ɗaukaka da rinjaye sai su kawo kai don su sami ganima, amma duk lokacin da wasu ayoyi na Alƙur'ani suka sauka suna maganar azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da narkonsa ga munafuƙai sai su ji kamar asirinsu ne zai tonu. Ba su son sauraron ayoyin da suke bayanin wani umurnin Allah ko haninsa, don haka sai su riƙa toshe kunnuwansu da 'yan yatsunsu. To sai Allah ya razanar da su da cewa, da ya ga dama da ya gusar musu da jinsu da ganinsu, su wayi gari dunɗum ba sa ganin komai ba sa jin komai sakamakon biris da gaskiya da suka yi. Domin kuwa Allah mai iko ne a kan komai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani da Tauhidin *Rububiyya* yana wajabta wa bawa ya yi imani da Tauhidin *Uluhiyya*.

2. Zamantowar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mahalicci komai, mai kuma bayar da arzuki ga bayinsa, shi ne ya sa ya cancanci a bauta masa shi kaɗai.

3. Taƙawa wani babban matsayi ne da ba a samun sa sai ta hanyar tsantsanta bauta ga Allah shi kaɗai.

4. A cikin ni'imomin na duniya ni'imar halitta ita ce mafi girma, domin duk wata ni'ima ta ginu ne a kanta.

5. Rahamar Allah ga bayinsa da bayanin girman Kudurarsa.

6. Allah yana ba da arzukinsa na duniya ga kowa da kowa; mumini da kafiri babu banbanci.

7. Haramcin sanya wa Allah kishiya ta hanyar shirka babba ko ƙarama.

Suratul Baƙara (21-22)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعْبُدُوا۟ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿٢١﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ فِرَٰشًا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءً
وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْ ۖ فَلَا تَجْعَلُوا۟ لِلَّهِ أَندَادًا وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٢٢﴾

21. Ya ku mutane, ku bauta wa Ubangijinku Wanda Ya halicce ku, da waɗanda suka gabace ku, ko kwa yi taƙawa.

22. Shi ne Wanda Ya sanya muku ƙasa ta zama shimfiɗa kuma Ya sanya muku sama ta zama gini kuma Ya saukar da ruwa daga sama Ya fitar muku da arziƙi na 'ya'yan itatuwa, don haka kada ku sanya wa Allah kishiyoyi alhalin kuna sane.

Bayan da Allah ya gama maganar kashe-kashen mutane, wato muminai masu taƙawa da siffofinsu da kafirai da siffofinsu da munafuƙai da nasu siffofin, sai kuma ya dunƙule su gaba ɗaya ya kirawo su zuwa ga bauta masa shi kaɗai. Da ma bautar ita ce manufar halittarsu, kamar yadda ya faɗa a cikin *Surat Az-Zariyati* aya ta 56. Sannan ya kafa musu manya-manyan hujjoji guda huɗu:
Hujja ta farko ita ce, shi ne wanda ya halicce su har da waɗanda suka gabace su, ya ba su ci da sha da buƙatunsu, don haka wanda ya yi halitta ai shi ne ya cancanci a bauta masa ba wani can daban ba.
Hujja ta biyu ita ce, shi ne wanda ya shimfiɗa musu ƙasa wadda suke yawo a kanta, su yi gine-ginensu duk a kanta. Lalle wanda ya yi wannan ai shi kaɗai ya cancanta a bautawa ba wani ba can daban ba.
Hujja ta uku ita ce, shi ne wanda ya ɗaukaka musu rufin samaniya, ya ƙawata shi da rana da wata da taurari, waɗanda suke amfanar su a rayuwarsu a bayan ƙasa. Wanda ya yi wannan aiki lalle shi ne ya cancanci bauta ba wani abu can daban ba.
Hujja ta huɗu ita ce, shi ne ya sauko musu da ruwan sama daga girgije, wanda suke sha su da dabbobinsu, kuma ya shayar musu da gonakinsu suka sami amfanin gona da kayan marmari iri-iri da ganyayyaki daban-daban. Lalle mai wannan aiki shi ne wanda ya cancanci bauta ba wani can daban ba. Waɗannan ayoyi suna nuni ne ga Tauhidin Rububiyya wanda yake jagoranci zuwa ga fahimtar Tauhidin Uluhiyya, wato bautar Allah shi kaɗai ba tare da yi masa kishiya ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani mu'ujiza ce daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Ya kuma ƙalubalanci duk masu fasahar Larabawa da su kawo kamarsa amma sun kasa.

2. Alƙur'ani ne mafi girmar mu'ujiza da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa (ﷺ).

3. Matsayin zama bawan Allah matsayi ne babba, saboda haka Allah ya zaɓi ya siffanta Manzonsa (ﷺ) da shi a irin wannan babban wuri.

4. Tabbatar wa kafurai cewa ba za su taɓa kawo wata magana kamar Alƙur'ani ba har abada.

5. Tabbatar da gaskiyar Alƙur'ani, domin ya nuna musu cewa ba za su kawo kamarsa ba har abada, kuma ga shi ya tabbata ɗin sun kasa kawo irinsa.

6. Wuta tana nan, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya halicce ta, ya kuma tanade ta domin kafirai.

Suratul Baƙara (23-24)

وَإِن كُنتُمْ فِي رَيْبٍ مِّمَّا نَزَّلْنَا عَلَىٰ عَبْدِنَا فَأْتُوا۟ بِسُورَةٍ مِّن مِّثْلِهِۦ وَٱدْعُوا۟ شُهَدَآءَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٢٣﴾ فَإِن لَّمْ تَفْعَلُوا۟
وَلَن تَفْعَلُوا۟ فَٱتَّقُوا۟ ٱلنَّارَ ٱلَّتِى وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلْحِجَارَةُ ۖ أُعِدَّتْ لِلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٤﴾

23. Kuma idan kun kasance cikin kokwanto game da abin da Muka saukar wa bawanmu, to ku zo da kwatankwacin sura ɗaya kamarsa, kuma ku kirawo masu taimakonku ba Allah ba in kun kasance masu gaskiya.

24. To idan har ba ku aikata hakan ba, kuma ba za ku taɓa iyawa ba, to ku kiyayi wata wuta wadda mutane ne da duwatsu makamashinta; an kuwa tanade ta domin kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah yana magana ne a kan gaskiyar annabcin Annabi (ﷺ) da gaskiyar Alƙur'anin da ya zo da shi. Allah ya kawo wata hujja ce mai ƙarfi wadda za ta kawo ƙarshen duk wani shaci-faɗin da kafirai suke yi game da Alƙur'ani. Allah ya bayyana cewa, shi fa Annabi (ﷺ), mutum ne kamarsu, yana magana da irin harshensu, kuma bai koyi wani ilimi na rubutu da karatu ba. To idan har shi ne ya ƙirƙiri Alƙur'ani da kansa ba wahayi Allah ya yi masa ba kamar yadda suke da'awa, to su ma ai Larabawa ne irinsa, sai su kawo ko da sura ɗaya kamar ta Alƙur'ani wajen hikima da fasaha. Kuma suna iya gayyato duk wani wanda suke ganin zai taimaka musu don cim ma wannan buƙatar tasu. Idan kuwa har suka kasa yin hakan, kuma ba za su iya ɗin ba, to su yi maza su karɓi gaskiya don kare kansu daga azabar Allah wadda wuta ce ba irin wadda suka sani ba a nan duniya, domin ita wannan makamashin hura ta mutane ne masu laifuka da duwarwatsu, kuma an riga an yi tanadin ta musamman domin kafirai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu mai shiga Aljanna sai wanda ya yi imani ya kuma aiki nagari.

2. Sakamakon 'yan Aljanna ya fi ayyukansu.

3. Cikar Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Sakamakon 'yan Aljanna ni'ima ce cikakkiya. Allah ya musu tanadin kayan daɗi iri-iri tare da ƙari.

5. Kwaɗaita wa zukata ni'imomin gidan Aljanna don zaburar da su su yi aiki nagari cikin nashaɗi da walwala.

Suratul Baƙara (25)

وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ كُلَّمَا رُزِقُواْ مِنۡهَا مِن ثَمَرَةٖ رِّزۡقٗا قَالُواْ هَٰذَا ٱلَّذِي رُزِقۡنَا مِن قَبۡلُۖ وَأُتُواْ بِهِۦ مُتَشَٰبِهٗاۖ وَلَهُمۡ فِيهَآ أَزۡوَٰجٞ مُّطَهَّرَةٞۖ وَهُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٥

25. Kuma ka yi albishir ga waɗanda suka yi imani kuma suka aikata ayyuka na ƙwarai cewa suna da wasu gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Duk sa'adda aka arzuta su da 'ya'yan itatuwa daga gare su sai su ce: "Wannan shi ne irin abin da aka arzuta mu da shi ɗazu." An kawo musu shi yana mai kama da juna, kuma suna da wasu mata tsarkaka a cikinsu, kuma su masu zama ne a cikinsu dindindin.

Bayan Allah ya ambaci sakamakon kafirci a ayar da ta gabata, sai kuma a nan ya ambaci sakamakon waɗanda suka yi imani, domin wannan shi ne tsarin salon Alƙur'ani wajen haɗa tsoratarwa da kwaɗaitarwa. Allah ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, ya yi albishir ga waɗanda suka yi imani da shi da abin da ya zo da shi na gaskiya, kuma suka aikata kyawawan ayyuka waɗanda suka nuna gaskiyar imaninsu, ya yi musu albishir da cewa, a lahira suna da wani sakamako na gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashin bishiyoyinsu da shuke-shukensu da ɗakunansu. Duk sa'adda aka kawo musu kayan marmari sai su zaci irin wanda aka taɓa kawo musu ne ba da daɗewa ba a Aljanna, saboda kamanninsu iri ɗaya ne, amma ba su san akwai banbanci ba wajen ɗanɗano. Sannan baya ga kayan marmari na Aljanna, har ila yau, suna da wasu mata na aure waɗanda suke tsarkaka ne daga duk wani abin ƙyama, kamar yadda suke da kyawawan halaye da ɗabi'u. Sannan wani abin kwantar da hankali gare su shi ne, za su dawwama a cikin wannan jin daɗi ba zai yanke musu ba har abada.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar wa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) siffar kunya kamar yadda ya dace da girmansa da ɗaukakarsa.

2. Haɗarin yin izgili da maganar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Duk wani abu na gaske da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da shi, ba ya halatta wani ya yi musun samuwarsa.

4. Wani abu guda yakan iya zama sanadiyar shiriyar wani, kuma sanadiyar ɓatan wani.

5. Haɗarin yin jayayya ba bisa gaskiya ba.

6. Ma'abota shiriya ko da kuwa su 'yan kaɗan ne a cikin mutane, to amma alherinsu da amfaninsu mai yawa ne. Su kuma ma'abota ɓata ko da suna da yawa, amma alherinsu da amfaninsu kaɗan ne a cikn al'umma.

7. Yin jayayya da hukuncin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) abu ne da yake kore imani.

8. Bai dace kunaya ta hana mai kira zuwa ga Allah ya bayyana wani hukunci na Allah ba ko faɗar wata gaskiya, ko da kuwa yin haka zai jawo masa suka daga masu suka.

Suratul Baƙara (26-27)

۞ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَسۡتَحۡيِۦٓ أَن يَضۡرِبَ مَثَلٗا مَّا بَعُوضَةٗ فَمَا فَوۡقَهَاۚ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَيَعۡلَمُونَ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّهِمۡۖ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَيَقُولُونَ مَاذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلٗاۘ يُضِلُّ بِهِۦ كَثِيرٗا وَيَهۡدِي بِهِۦ كَثِيرٗاۚ وَمَا يُضِلُّ بِهِۦٓ إِلَّا ٱلۡفَٰسِقِينَ ٢٦ ٱلَّذِينَ يَنقُضُونَ عَهۡدَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مِيثَٰقِهِۦ وَيَقۡطَعُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٢٧

26. Lalle Allah ba Ya jin kunyar buga kowanne irin misali komai ƙanƙantarsa, sauro da abin ya fi shi. To amma waɗanda suka yi imani suna sanin cewa, lalle shi (wannan misali) gaskiya ne daga Ubangijinsu. Amma waɗanda suka kafirta sai su riƙa cewa: “Me Allah Yake nufi da wannan misalin?” Yana kuwa ɓatar da mutane da yawa da shi, kuma Ya shiryar da mutane da yawa da shi, kuma ba kowa Yake ɓatarwa da shi ba sai fasiƙai.

27. Waɗanda suke warware alkawarin Allah bayan ƙulla shi, kuma suke yanke abin da Allah Ya yi umarni a sadar da shi, kuma suke ɓarna a bayan ƙasa. Waɗannan su ne cikakkun hasararru.

A waɗannan ayoyi kuma Allah yana sanar da cewa, ba ya jin kunyar bayar da wani misali da kowane abu na halittarsa komai ƙanƙantarsa kuwa, kamar sauro da abin da ya ɗara shi girma ko ƙanƙanta saboda hikimar da take cikin waɗannan misalan da fito da bayanai dalla-dalla don a gane. To yayin da Allah ya ba da irin waɗannan misalan masu sauraro sukan kasu gida biyu; kashi na farko su ne muminai masu yaƙinin cewa, wannan misali da Allah ya bayar gaskiya ne. Ƙashi na biyu kuma su ne kafirai, sai wannan misali ya ɗimautar da su har su nuna rashin yardarsu a kai, suna ganin don me Allah zai riƙa bayar da irin

waɗannan misalan, sai su ƙara kafircewa a kan kafircinsu na farko. Sun kasa gane cewa, hikimar da ta sa Allah yake yin haka ita ce don ƙara bambancewa tsakanin mumini da kafiri. Don haka waɗannan misalan sukan zama sanadiyyar shiriyar muminai da dama, sannan kuma sukan zama sanadiyyar ɓacewar kafirai da dama. To amma fa ba wasu ne suke ɓacewa ta hanyar waɗannan misalan ba sai waɗanda suke kangare wa ɗa'ar Allah, waɗanda suke warware duk wani alƙawari da suka yi tsakaninsu da Allah, sannan suke yi wa shari'ar Allah karan-tsaye, kamar ƙin sadar da zumunci, sannan su yi ta yaɗa ɓarna ta kafirci da munafinci da zalunci a bayan ƙasa. To irin waɗannan halaye nasu su ne suka yi katutu a zukatansu har suka toshe musu zukata ya zamana ba su fahimtar duk wani misali da Allah zai bayar a Littafinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cikar Kudurar Allah da tabbatar da tashi bayan mutuwa, kuma makomar duk halitta zuwa ga Allah take.

2. Ni'imar samuwa daga babu, ni'ima ce da ta cancanci a gode wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a kanta, a bauta masa shi kaɗai kada a kafirce masa.

3. Bayanin halaccin komai daga abubuwan da Allah ya hore wa ɗan'adam domin amfaninsa, sai abin da nassi ya bayyana haramcinsa.

4. Allah ya hore komai a duniya domin amfanin ɗan'adam, don haka bai dace ga ɗan'adam ya bautar da kansa ga duniya ba, idan kuma ya yi haka to ya hallaka kansa da kansa.

5. Tunatar da ɗan'adam ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa domin ya gode masa ta hanyar bauta masa shi kaɗai.

6. Yalwar ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da gamewarsa ko'ina.

Suratul Baƙara (28-29)

كَيْفَ تَكْفُرُونَ بِٱللَّهِ وَكُنتُمْ أَمْوَٰتًا فَأَحْيَٰكُمْ ۖ ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يُحْيِيكُمْ ثُمَّ إِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٢٨﴾ هُوَ ٱلَّذِى خَلَقَ لَكُم مَّا فِى ٱلْأَرْضِ جَمِيعًا ثُمَّ ٱسْتَوَىٰٓ إِلَى ٱلسَّمَآءِ فَسَوَّىٰهُنَّ سَبْعَ سَمَٰوَٰتٍ ۚ وَهُوَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٢٩﴾

28. Ta yaya kuke kafirce wa Allah alhalin a da kun kasance matattu, sannan Ya raya ku, sannan zai kuma mayar da ku matattu sannan Ya raya ku (a karo na biyu) sannan zuwa gare Shi ake mayar da ku?

29. Shi ne wanda Ya halitta muku abin da yake cikin ƙasa gaba ɗaya, sannan Ya nufi sama Ya daidaita su sammai bakwai, kuma Shi Masanin komai ne.

A nan Allah yana nuna mamakin yadda waɗannan kafirai masu kafirce masa da kafirce wa shiriyar da ya aiko Manzonsa (ﷺ) da ita, tare da cewa, dalilai masu nuna girman Kudurarsa sun bayyana a sarari. Daga cikin irin waɗannan dalilai akwai cewa Allah ne ya kashe su sau biyu ya kuma raya su sau biyu. Kashewa ta farko, ita ce lokacin da babu su sannan ya samar da su; kashewa ta biyu, ita ce lokacin da yake karɓar rayukansu yayin mutuwarsu. Rayawa ta farko ita ce, halittarsu daga babu, sannan rayawa ta biyu ita ce, tayar da su daga ƙaburburansu bayan sun mutu. Su kansu kafirai za su tabbatar da hakan ranar gobe alƙiyama, kamar yadda ya zo a '*Suratu Ghafir*', aya ta 11.

Sannan yana daga cikin manya-manyan dalilan cancantar a bauta wa Allah shi kaɗai, cewa ya halicci abin da yake cikin ƙasa gaba ɗaya domin amfanin ɗan’adam, sannan bayan ya gama halittar ƙasa ya nufi sama ya yi mata kyakkyawar halitta ya mayar da ita sammai bakwai. Kuma shi mai cikakken sani ne ga duk abin da ya halitta, kuma iliminsa ya game ko’ina.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan jarrabi bayinsa da abin da ya ga dama. Allah ya jarrabi mala'ikunsa da halittar Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai ya bayyana a gare su cewa, ba su gane hikimar da take tattare da halittar Adamu da ta 'ya'yansa a bayansa ba.

2. Dacewar yabo ga wanda ya cancanci yabo da bayyana falalar mai falala, musamman ga wanda bai san shi ba, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

3. Mala'iku suna ƙin aukuwar ɓarna a bayan ƙasa.

4. Halaccin yin tambaya game da hikimar yin wata halitta idan ya kasance manufar tambayar ita ce neman sani, ba nuna rashin yarda ba.

5. Mala'iku ba su san gaibu ba.

6. Falalar Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da matsayinsa a wurin Allah.

7. Allah ya yi magana da Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), don haka shi Annabi ne da Allah ya yi magana da shi, kamar yadda ya zo a cikin hadisin da Ibn Hibban ya ruwaito. [Ibn Hibban #6190].

8. Bayanin ladabin mala'iku ga Ubangijinsu.

9. Dalilin fifita annabawa a kan mala'iku.

10. Girman matsayin ilimi da falalarsa da falalar mai ilimi.

11. Allah ne kaɗai masanin gaibun sammai da ƙasa da abin da yake ɓoye a cikin zukatan bayinsa.

Suratul Baƙara (30-33)

وَإِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّي جَاعِلٌ فِي ٱلْأَرْضِ خَلِيفَةً ۖ قَالُوٓاْ أَتَجْعَلُ فِيهَا مَن يُفْسِدُ فِيهَا وَيَسْفِكُ ٱلدِّمَآءَ وَنَحْنُ نُسَبِّحُ بِحَمْدِكَ وَنُقَدِّسُ لَكَ ۖ قَالَ إِنِّيٓ أَعْلَمُ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٣٠﴾ وَعَلَّمَ ءَادَمَ ٱلْأَسْمَآءَ كُلَّهَا ثُمَّ عَرَضَهُمْ عَلَى ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ فَقَالَ أَنۢبِـُٔونِي بِأَسْمَآءِ هَٰٓؤُلَآءِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٣١﴾ قَالُواْ سُبْحَٰنَكَ لَا عِلْمَ لَنَآ إِلَّا مَا عَلَّمْتَنَآ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٣٢﴾ قَالَ يَٰٓـَٔادَمُ أَنۢبِئْهُم بِأَسْمَآئِهِمْ ۖ فَلَمَّآ أَنۢبَأَهُم بِأَسْمَآئِهِمْ قَالَ أَلَمْ أَقُل لَّكُمْ إِنِّيٓ أَعْلَمُ غَيْبَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَأَعْلَمُ مَا تُبْدُونَ وَمَا كُنتُمْ تَكْتُمُونَ ﴿٣٣﴾

30. Kuma ka tuna sa'adda Ubangijinka Ya ce da mala'iku: “Lalle ni zan sanya wani halifa a bayan ƙasa.” Suka ce: “Yanzu za Ka sanya mata wanda zai yi ɓarna a cikinta kuma ya zubar da jini, alhali ga mu muna tasbihi tare da gode Maka, kuma muna tsarkake Ka?” (Allah) Ya ce: “Ni fa tabbas Na san abin da ku ba ku sani ba.”

31. Kuma sai (Allah) Ya koya wa Adamu dukkan sunaye (na abubuwa) sannan Ya kawo su gaban mala'iku, sai Ya ce: “Ku faɗa min sunayen waɗannan abubuwan in kun zamanto masu gaskiya.”

32. Sai suka ce: “Tsarki ya tabbata a gare Ka, ba mu da wani ilimi sai wanda Ka sanar da mu. Lalle Kai ne cikakken Masani, Mai hikima.”

33. Ya ce: “Ya Adamu faɗa musu sunayensu.” Yayin da ya faɗa musu sunayensu, sai (Allah) Ya ce: “Ba Na faɗa muku cewa, lalle Ni ne Nake sane da gaibin sammai da ƙasa ba, kuma Nake sane da abin da kuke bayyanawa da kuma abin da kuke ɓoyewa ba?”

Bayan da Allah ya gama maganar halittar ƙasa da abubuwan da ke cikinta, da halittar sammai da abubuwan da suka ƙunsa, sai ya shiga bayanin halittar ɗan’adam na farko, wato Annabi Adam (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda Allah ya damƙa masa alhakin raya wannan ƙasar ta hanyar bin tsarin da ya haɗo shi da shi na shiriya, da kuma shimfiɗa adalci a bayan ƙasa da bauta masa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba.
Allah yana ba wa Annabinsa (ﷺ) labarin abin da ya faɗa wa mala’iku na cewa, zai halicci wata halitta da zai ajiye a bayan ƙasa, waɗanda wasunsu za su riƙa maye gurbin wasu, wato Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da zurriyarsa. Sai mala’ikun suka yi wa Allah tambayar neman sani, amma ba ta jayayya ba, suka ce: “Shin za ka ajiye waɗanda za su riƙa ɓarna a bayan ƙasa, suna kashe juna, alhali ga mu muna yi maka tasbihi da tsarkake ka a ko da yaushe? Me zai hana ka saka mu a madadinsu?” Sai Allah ya faɗa musu cewa, akwai abin da ba su sani ba na maslahar da ke tattare da sanya Adamu ya zama khalifa a bayan ƙasa.
Daga nan sai Allah ya fara nuna wa mala’ikun wasu hikimomin da yake nufi game da halittar Annabi Adam (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai ya koyar da shi sunayen dukkanin abubuwa sannan ya nuna wa mala’iku su ya nemi su faɗa masa sunayensu idan har gaskiya suke a da’awar sun san abubuwa, kuma sun fi Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cancatar khalifanci a bayan ƙasa. To fa a nan take sai mala’iku suka tsarkake Ubangijinsu, kuma suka ƙara tabbatar da cewa, lalle su ba komai suka sani ba, Allah ne ya san komai kuma shi ne yake saka duk wani abu a mahallinsa da ya dace. To daga nan sai Allah ya umarci Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya faɗa musu sunayen waɗannen abubuwan. Yayin da ya faɗa musu sai suka fahimci fifikon da Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake da shi a kansu, kuma sai Allah ya ƙara tuna musu cewa, da man ai shi ne masanin gaibun da yake sama da wanda yake ƙasa, kuma ya san abin da suke bayyanawa da abin da suke ɓoyewa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babbar karramawar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da zurriyarsa.

2. Bayanin kafircin Iblis da girman kansa wajen ƙin bin gaskiya da wulaƙanta halittar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Falalar mala'iku da yadda suke amsa umarnin Allah cikin gaggawa.

4. Duk hukunci na Allah ne, shi yake hukunta abin da ya ga dama. Ya yi umarni a yi wa wanda ya ga dama sujjada, ya hana yi wa wani sujjada idan ya ga dama, kamar yadda ya hana wannan al'umma yi wa wani sujjada ba shi ba.

5. Wajabcin bin umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ko da ya saɓa wa son zuciya.

6. Girman kai game da yi wa Allah ɗa'a yakan iya kai bawa zuwa ga kafurci.

7. Bayani game da baiwar da Allah ya yi wa Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da matarsa Hauwa ta shiga gidan Aljanna.

8. 'Ya'yan marmarin gidan Aljanna ana samun su a koyaushe ake da buƙatarsu.

9. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan iya jarrabar bayinsa ta hanyar hana su wasu abubuwa.

10. Idan shari'a ta haramta wani abu to sai ta hana duk wani abu da zai iya kai mutum ga abin da aka harmta masa.

11. Mahallin zama da samun abinci suna daga cikin manya-manyan ni'imomi ga ɗan'adam.

12. Abubuwan da aka halatta sun fi waɗanda aka haramta yawa.

13. Haɗarin saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), domin yakan yi sanadiyyar bawa ya rasa wata babbar ni'ima ta Ubangijinsa.

14. Samuwar Aljanna tun gabanin halittar ɗan'adam.

15. Kiyayyar Iblis ga ɗan'adam da ƙoƙarinsa koyaushe na ya ga ya ɓatar da shi, ya jefa shi cikin saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya raba shi da ni'imar Allah.

16. Babu wani wuri da ɗan'adam zai iya rayuwa sai a bayan ƙasa. Duk wani yunƙuri da fafutuka da wasu suke yi na neman wani wuri na daban da za a rayu a cikinsa ba doron ƙasa ba, to aikin banza ne ba zai yi nasara ba.

17. Duniya ba matabbata ce ba. Rayuwar ɗan'adam a cikinta iyakantacciya ce.

18. Rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga ɗan'adam da ya tanada masa matsuguni tun kafin ya saukar da shi ƙasa.

19. Baiwar da Allah ya yi Adamu da Hauwa'u; bai bar su cikin zunubi ba, ya buɗe musu ƙofar tuba, suka kuma tuba Allah ya karɓi tubansu ya ƙara musa daraja da matsayi a wurinsa.

20. Falalar tuba zuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Idan bawa ya yi laifi ya kuma tuba zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tuba ta gaskiya, to Allah zai yafe masa ya karɓi tubarsa.

21. Wani abu marar daɗi zai iya faruwa ga bawa, amma daga ƙarshe ya zamo masa alheri. Don haka koyaushe bawa ya zamanto yana mayar da al'amarinsa ga Allah yana neman yardarsa cikin komai.

22. Tun farkon saukowar ɗan'adam bayan ƙasa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗo shi da shiriya da tsarin da zai rayu a kansa, saboda haka babu wani lokaci da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bar ɗan'adam sakaka ba tare da wata shiriya ba.

23. Bin shiriyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da tsarinsa kaɗai ne zai haifar wa da ɗan'adam nutsuwa da kwanciyar hankali a rayuwarsa ta duniya da ta lahira. Kauce wa tsarin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne yake buɗe masa duk wata ƙofar fitina da rashin zaman lafiya.

24. Daga cikin dalilan dauwama a cikin wutar Jahannama akwai ƙaryata ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Wanda ya ƙaryata ayar Allah ɗaya da ya saukar to ya kafirta, kuma zai dauwama a cikin wuta ranar alƙiyama.

Suratul Baƙara (34-39)

وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُواْ لِأَدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبْلِيسَ أَبَىٰ وَٱسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٣٤﴾ وَقُلْنَا يَٰٓـَٔادَمُ ٱسْكُنْ أَنتَ وَزَوْجُكَ ٱلْجَنَّةَ وَكُلَا مِنْهَا رَغَدًا حَيْثُ شِئْتُمَا وَلَا تَقْرَبَا هَٰذِهِ ٱلشَّجَرَةَ فَتَكُونَا مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٣٥﴾ فَأَزَلَّهُمَا ٱلشَّيْطَٰنُ عَنْهَا فَأَخْرَجَهُمَا مِمَّا كَانَا فِيهِ ۖ وَقُلْنَا ٱهْبِطُواْ بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ عَدُوٌّ ۖ وَلَكُمْ فِى ٱلْأَرْضِ مُسْتَقَرٌّ وَمَتَٰعٌ إِلَىٰ حِينٍ ﴿٣٦﴾ فَتَلَقَّىٰٓ ءَادَمُ مِن رَّبِّهِۦ كَلِمَٰتٍ فَتَابَ عَلَيْهِ ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٣٧﴾ قُلْنَا ٱهْبِطُواْ مِنْهَا جَمِيعًا ۖ فَإِمَّا يَأْتِيَنَّكُم مِّنِّى هُدًى فَمَن تَبِعَ هُدَاىَ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٣٨﴾ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٣٩﴾

34. Kuma ka tuna lokacin da Muka ce wa mala'iku: “Ku yi sujjada ga Adamu.” Sai duk suka yi sujjada, in ban da Iblis, sai shi ya ƙi, ya kuma yi girman kai, kuma ya tabbata cikin kafirai.

35. Kuma Muka ce: “Ya kai Adamu, ka zauna gidan Aljanna kai da matarka, kuma ku ci (kayan marmarinta) cikin yalwa a duk inda kuka ga dama, kada kuma ku kuskura ku kusanci wannan bishiyar, sai ku kansance daga cikin azzalumai.”

36. Sai Shaiɗan ya sa suka zame, sai ya fitar da su daga ni'imar da suke ciki. Sai Muka ce: “Ku sauko ƙasa sashinku yana mai gaba da sashi; kuma kuna da mazauni a bayan ƙasa da wani jin daɗi zuwa wani ɗan lokaci.”

37. Sai Adamu ya karɓi wasu kalmomi daga Ubangijinsa (na neman gafara), sai Ya yafe masa; lalle Shi ne Mai yawan karɓar tuba kuma Mai yawan jin ƙai.

38. Muka ce: “Dukkanku ku sauko daga cikinta, sannan idan wata shiriyata ta zo muku, to waɗanda suka bi shiriyata, babu wani tsoro a tare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

39. Kuma waɗanda suka kafirta suka kuma ƙaryata ayoyinmu, waɗannan su ne 'yan wuta, su masu dawwama ne a cikinta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da Manzonsa (ﷺ) cewa, ya umarci mala’iku da su faɗi su yi sujjada ga Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kuma nan take suka karɓa umarninsa suka faɗi suka yi masa sujjada, sai Iblis shi kaɗai ya nuna girman kai, ya bijire wa umarnin Allah ya ƙi yi wa Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sujjada. Sai Allah ya umarci Annabi Adamu da matarsa Hawwa’u da su shiga Aljanna su zauna a cikinta, ya yi musu izini da su ci komai na kayan marmari da ke cikinta a wadace, in ban da wata itaciya guda ɗaya wadda ya nuna

musu ita ya ce, su nisance ta kada su ci ‘ya’yanta domin idan har suka ci to sun ƙetare iyakokin da ya gindaya musu.
Sai Shaiɗan ya yaudare su ta hanyar yi musu waswasi ya sa suka ci ‘ya’yan wannan bishiyar, wanda a dalilin haka Allah ya fitar da su daga gidan Aljanna, ya umarce su da su dawo bayan ƙasa su zauna, wanda a nan ne ƙiyayya za ta bayyana a tsakaninsu, kuma nan ne wurin rayuwarsu, idan kuma sun mutu a cikinta ne za a binne su har zuwa lokacin tashin alƙiyama. Bayan haka kuma sai Allah ya laƙanta wa Annabi Adamu wasu kalmomi da zai faɗa Allah ya yafe masa laifinsa, sai ya faɗa shi da matarsa, kuma Allah ya karɓi tubansu domin shi ne mai yafe wa muminai duk wani laifi da za su yi su nemi ya yafe musu.
Daga nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Adamu da Hawwa’u da Iblis da su sauko daga gidan Aljanna gaba ɗaya, kuma ya faɗa musu cewa, idan wani abu na shiriya ya zo musu, littafi ne ko kuma wani manzo ne wanda zai nusar da su hanyar shiriya, idan har suka karɓe shi suka yi aiki da shi to za su samu cikakken zaman lafiya da farin ciki na har abada. Wanda kuwa ya bijire ya ƙi yarda da gaskiya ya ƙaryata ayoyin Allah, to wannan sakamakonsa gidan wuta ne, kuma zai zauna ciki har abada babu fita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tuna wa bawa ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa ya fi zama hujja a kansa, yakan kuma sanya shi ya karɓi gaskiya da wuri.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Banu Isra’ila ni’ima babba.

3. Idan Allah ya yi wa kakanni ni'ima to kamar ya yi wa jikokinsu ne, domin birbishin ni'imar da ya yi musu dole sai ta shafe 'ya'yansu da jikokinsu. Kuma ba don ya kuɓutar da kakanninsu ba ai da su ma ba a same su ba.

4. Wajabcin gode wa ni'imomin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da guje wa butulce masa.

5. Wajibi ne wanda ya yi bakance na alheri ya cika bakancensa.

6. Alƙur'ani littafi ne da yake gaskata littattafan da suka gabace shi, yake kuma tabbatar da abin da suka zo da shi na gaskiya da kaɗaita Allah. Hakanan su ma littaffan da suka gabata suna tabbatar da gaskiyar Alƙur'ani da ingancin manzancin Annabi (ﷺ).

7. Duk wanda ya fara kafirce wa Allah, kuma ya zamanto abin koyi ga na bayansa cikin kafirci, to lalle zai ɗauki nayin zunubansa da na waɗanda suka ɓace a dalilinsa.

8. Duk wanda ya sayar da ayoyin Allah da 'yan kuɗi kaɗan, to lalle ya yi koyi ne da Yahudawa.

9. Wajabcin bayanin gaskiya ga mutane da haramcin ɓoye ta. Idan kuma wani ya ɓoye gaskiya saboda wani abin duniya da zai samu, to wannan laifinsa ya fi tsanani.

10. Wajibi mai karantawa ko da'awa ya riƙa ƙoƙarin yaye wa mutane shubuhohi da yi musu bayanin duk abin da ba su fahimta ba. Kuma duk wanda yake a wurin da babu wanda zai koyar da mutane sai shi, to dole ne ya tashi ya koyar da su abin da suke buƙata na addini.

11. Haramun ne a riƙa ƙawata ƙarya don a jawo hankalin mutane zuwa gare ta, ko kuma gurɓata gaskiya don mutane su nisance ta.

12. Yana daga cikin salon Yahudawa na yaɗa ɓarna shi ne su riƙa cakuɗa ƙarya da gaskiya.

13. Mummunan tasirin ɓatattun malamai.

14. Muhimmancin bayyana gaskiya domin shiryar da ɓatattu zuwa ga miƙaƙƙiyar hanya.

15. Kamalar wanann shari'a ta Musulunci, domin ta zo da abin da zai tsarkake zukata da kuma dukiyoyi.

16. Falalar salla a cikin jama'a, domin za a ninnika wa masallaci ladansa.

17. Aikin mutum ya riƙa saɓa wa maganarsa abu ne mai haɗari babba.

18. Laifin wanda ya san hukunci ya saɓa masa ya fi na wanda ya jahilci hukucin tun farko.

19. Hankali yakan hana mai shi aikata mummunan aiki yana sane.

20. Girman sha'anin salla, sai dai tana da sauƙi ga wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sauwaƙe masa.

21. Kwaɗaitarwa a kan neman sahhale al'amuran rayuwa ta hanyar salla da haƙuri.

22. Girman falalar haƙuri.

23. Sakankancewa da haɗuwa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanya bawa ya dage wajen kyautata ayyukansa, domin ya samu yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

24. Tabbatar da ranar lahira wadda ita ce makomar dukkan halittu.

Suratul Baƙara (40-46)

يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتِيَ ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ وَأَوۡفُواْ بِعَهۡدِيٓ أُوفِ بِعَهۡدِكُمۡ وَإِيَّيَ فَٱرۡهَبُونِ ٤٠ وَءَامِنُواْ بِمَآ أَنزَلۡتُ مُصَدِّقٗا لِّمَا
مَعَكُمۡ وَلَا تَكُونُوٓاْ أَوَّلَ كَافِرِۭ بِهِۦۖ وَلَا تَشۡتَرُواْ بِـَٔايَٰتِي ثَمَنٗا قَلِيلٗا وَإِيَّيَ فَٱتَّقُونِ ٤١ وَلَا تَلۡبِسُواْ ٱلۡحَقَّ بِٱلۡبَٰطِلِ وَتَكۡتُمُواْ ٱلۡحَقَّ وَأَنتُمۡ
تَعۡلَمُونَ ٤٢ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱرۡكَعُواْ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ٤٣ * أَتَأۡمُرُونَ ٱلنَّاسَ بِٱلۡبِرِّ وَتَنسَوۡنَ أَنفُسَكُمۡ وَأَنتُمۡ تَتۡلُونَ ٱلۡكِتَٰبَۚ
أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٤٤ وَٱسۡتَعِينُواْ بِٱلصَّبۡرِ وَٱلصَّلَوٰةِۚ وَإِنَّهَا لَكَبِيرَةٌ إِلَّا عَلَى ٱلۡخَٰشِعِينَ ٤٥ ٱلَّذِينَ يَظُنُّونَ أَنَّهُم مُّلَٰقُواْ رَبِّهِمۡ وَأَنَّهُمۡ إِلَيۡهِ رَٰجِعُونَ
٤٦

40. Ya ku 'ya'yan Isra'ila, ku tuna ni'imata da Na yi muku, kuma ku cika alƙawarina zan cika muku alkawarinku, kuma ku tsorace Ni Ni kaɗai.

41. Kuma ku yi imani da abin da Na saukar yana mai gaskata abin da yake tare da ku (na wahayi), kada kuma ku zama farkon (jinsinku) da zai kafirce masa, kuma kada ku sayar da ayoyina da ɗan kuɗi kaɗan, kuma ku kiyaye dokokina.

42. Kada kuma ku gauraya gaskiya da ƙarya, kuma ku ɓoye gaskiya, alhalin kuna sane.

43. Kuma ku tsayar da salla, ku kuma ba da zakka, kuma ku yi ruku'i tare da masu ruku'i.

44. Shin yanzu kwa riƙa umartar mutane da ayyukan alheri ku kuma kuna mantawa da kawunanku, alhalin kuna karanta Littafi? Ashe ba za ku hankalta ba?

45. Kuma ku nemi agaji ta hanyar haƙuri da kuma salla, kuma lalle ita (salla) babban abu ne sai dai ga masu ƙasƙantar da kai.

46. Waɗanda suka tabbatar da cewa, su masu haɗuwa ne da Ubangijinsu, kuma su zuwa gare Shi suke komawa.

Bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci asalin halittar ɗan'adam da kuma ƙiyayyar Shaiɗan a gare shi, ya kuma faɗa wa Annabi Adamu da zurriyarsa bayan ya saukar da su bayan ƙasa, ya ce kuma zai zo musu da shiriya wadda duk wanda ya bi ta to ya kuɓuta daga kowane irin tsoro da baƙin ciki. Sannan ya yi kashedi ga waɗanda za su saba wa wannan shiriyar da fuskantar wata azaba mai tsanani ta wutar Jahannama.
To, a waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayani a kan Banu Isara'la ne waɗanda suka yi ƙaurin suna wajen nuna wa annabawansu taurin kai da butulce wa ni'imar Allah mai yawa da ya yi musu. Banu Isra'ila su ne jikokin Annabi Yaƙuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). A nan Allah yana nuna musu ni'imar da ya yi musu, kuma yana umartar su da su zama masu cika alƙawari, idan sun yi hakan shi kuma zai ba su abin da ya alƙawarta musu na shiga Aljanna. Ya tunatar da su kan su ji tsoronsa shi kaɗai sannan ya umarce su da su gaskata Alƙur'ani ta hanyar imani da shi da aiki da abin da ya ƙunsa na shari'a, saboda yana ɗauke da irin abin da ya zo cikin littafin Attaura ta Annabi Musa wanda ya danganci Tauhidi, don haka ya gargaɗe su da kada su zama su ne na farko da za su kafirce wa wannan Alƙur'ani da wanda aka saukar wa Alƙur'anin shi ne Annabi Muhammadu (ﷺ). Har ila yau ya hana su musanya ayoyin Allah da wani abu na ƙyale-ƙyalen duniya wanda a wurin Allah ba a bakin komai yake ba, ta hanyar watsi da imani da Alƙur'ani da abin da Manzon Allah ya zo da shi da ɓoye gaskiya da take ta.
Hakanan ya hana su cakuɗa ƙarya da gaskiya tare da ɓoye gaskiya, alhalin sun san irin illar da take cikin yin hakan. Kuma ya umarce su da tsayar da salla da rukunnanta da wajibanta, su bayar da zakkar dukiyarsu, sannan su tsayar da salla cikin jam'i tare da sauran muminai. Sannan Allah ya zarge su da abin da suke yi na umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna, amma kuma su a karan kansu ba sa aiki da abin da suke yin umarni da shi, alhali ga shi suna karanta Attaura sun san abin da yake cikinta na hukunce-hukunce, wanda yin haka ya saba wa aikin mutane masu hankali. Daga bisani Allah ya umarce su da su nemi taimako ta hanyar tsayar da salla da haƙuri cikin duk al'amura, duk da cewa salla tana da nauyi ga wasu in ban da masu ƙasƙantar da kansu ga Allah waɗanda su ne suka tabbatar da cewa, akwai ranar gamuwarsu da Ubangijinsu wadda ita ce ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ga Banu Isra'ila su gode wa ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu. Yana daga cikin godiyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) su bi Annabinsa Muhammadu (ﷺ) da ya aiko musu.

2. Fifita Banu Isra'ila a kan sauran mutane fifiko ne da ya shafi zamaninsu kaɗai, saboda yawancinsu a wancan lokacin suna da ilimi da imani da kuma ayyuka nagari.

3. Bayanin tsananin ranar alƙiyama wanda a cikinsa duk wata dangantaka ba za ta amfani kowa ba wajen ta kare shi masa azabar Allah ko ya samu sassauci, saɓanin rayuwar duniya.

4. Kafirai ba za su sami ceto ko fansa ko taimako ba a ranar alƙiyama.

Suratul Baƙara (47-48)

يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتِيَ ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ وَأَنِّي فَضَّلۡتُكُمۡ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ٤٧ وَٱتَّقُواْ يَوۡمٗا لَّا تَجۡزِي نَفۡسٌ عَن نَّفۡسٖ شَيۡـٔٗا وَلَا يُقۡبَلُ مِنۡهَا شَفَٰعَةٞ وَلَا يُؤۡخَذُ مِنۡهَا عَدۡلٞ وَلَا هُمۡ يُنصَرُونَ ٤٨

47. Ya ku 'ya'yan Isra'ila ku tuna ni'imata da Na yi muku, kuma Ni Na fifita ku a kan sauran mutanen duniya.

48. Kuma ku kiyayi wata rana da babu wani (mai) rai da zai isar wa da wani (mai) rai komai a cikinta; kuma ba za a karɓi wani ceto daga gare shi ba, kuma ba za a karɓi wata fansa daga gare shi ba, kuma ba za a taimaka musu ba.

Daga nan har zuwa aya ta 61 Allah ya bayyana irin ni’imomi daban-daban da ya yi ta yi wa Banu Isra’ila, amma maimakon su yi masa godiya ta hanyar biyayya ga Manzonsa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai suka riƙa nuna butulci da kangare wa umarnin Allah da ƙin biyayya da girmamawa ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya kirawo su yana tuna musu irin ni’imominsa ga iyayensu wanda ko la’alla yin hakan zai sa musu godiyar Allah da shiga cikin addinin gaskiya na Musulunci. Ya kuma tuna musu yadda ya fifita su a kan sauran al’ummomi na zamaninsu ta hanyar aiko musu da manzanni daga cikinsu da saukar musu da littattafai, sannan ya tsoratar da su azabar lahira, ranar da kowa ta kansa yake, babu wani wanda zai iya magance wa ɗan’uwansa wata matsala a wannan rana, ko ya fanshi ɗan’uwansa kafiri ta hanyar ceto shi daga azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babbar ni'ima ce ga mutane Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuɓutar da su daga hannun maƙiyansu azzalumai.

2. Bayanin makircin Fir'auna da jama'arsa yayin da suka yi mummunan tanadin rage yawan Banu Isra'ila ta hanyar yanka 'ya'yansu maza da barin mata da rai domin su riƙa yi musu aikin bauta a gidajensu.

3. Daga cikin munanan ɗabi'un azzalumi akwai wulaƙanta mutane da tirsasa su su riƙa yi musu hidima ba da son ransu ba.4. Ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yayi wa Banu Isra'ila ta hallakar da maƙiyinsu a gaban idanuwansu, domin su huce haushin azabar wulaƙanci da suka gana musu.

5. Girman Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wadda ta bayyana yayin da ya raba kogi gida biyu, kowane tsagi kamar wani ƙaton dutse.6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Fir'auna ƙarshensa, saboda da ya tashi hallaka shi sai ya hallaka shi da abin da ya kasance yana yi wa mutanensa alfahari da shi, watau ruwa. [Dubi, Suratuz *Zukhruf*, aya ta 51]

وَإِذۡ نَجَّيۡنَٰكُم مِّنۡ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ يَسُومُونَكُمۡ سُوٓءَ ٱلۡعَذَابِ يُذَبِّحُونَ أَبۡنَآءَكُمۡ وَيَسۡتَحۡيُونَ نِسَآءَكُمۡۚ وَفِي ذَٰلِكُم بَلَآءٞ مِّن رَّبِّكُمۡ عَظِيمٞ ٤٩ وَإِذۡ فَرَقۡنَا بِكُمُ ٱلۡبَحۡرَ فَأَنجَيۡنَٰكُمۡ وَأَغۡرَقۡنَآ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ وَأَنتُمۡ تَنظُرُونَ ٥٠

49. Kuma ku tuna lokacin da Muka kuɓutar da ku daga jama'ar Fir'auna waɗanda suke ɗanɗana muku mummunar azaba, suna yanka 'ya'yanku maza, kuma suna ƙyale 'ya'yanku mata. A cikin wannan lamari akwai babbar jarraba daga Ubangijinku.

50. Kuma ku tuna lokacin da Muka raba muku kogi, sai Muka kuɓutar da ku, kuma Muka nutsar da jama'ar Fir'auna, alhalin kuna kallo.

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tuna wa Banu Isra’ila irin yadda Fir’auna shi da magoya bayansa suka riƙa gana wa iyayensu azaba ta hanyar yanka ‘ya’yansu maza da ƙyale mata don su bautar da su a gidajensu, amma sai Allah ya kuɓutar da su daga wannan matsananciyar azaba. Wannan kuwa ba ƙaramar ni’ima ce gare su ba, don haka ya zama wajibi a kansu su yi wa Allah godiya.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata musu wata ni’imar ta daban wadda ya yi musu lokacin da Fir’auna da rundunarsa suka biyo su don hallakar da su. Bayan sun iso gaɓar kogi sai Allah ya umarci Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya daki kogi da sandarsa, sai ko ya rabu gida biyu, suka ga hanya totar a gabansu suka bi suka ƙetare. Lokacin da Fir’auna ya iso shi da rundunarsa suka fara bi ta wannan hanyar sai Allah ya mayar da wannan kogi ya haɗe da su suka halaka gaba ɗaya, mutanen Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suna gani domin su huce haushin abin da ya faru gare su a baya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Banu Isra'ila ba su da wani uzuri na aikata shirka. Sai dai kawai sun yi amfani da tafiyar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wajen ganawa da Allah, sai suka shiga aikata kafirci da ɓarna a bayan ƙasa.

2. Rashin samuwar wani malami a cikin jama'a yakan haddasa bayyanar shirka da bidi'a a tsakaninsu.

3. Bayanin cewa bautar wanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) babban zalunci ne.

4. Bayanin yalwar haƙurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma Allah yana gafarta shirka ga wanda ya tuba.

5. Hukunci mai tsanani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Banu Isra'ila yayin da ya umarce su da su kashe kawunansu kafin ya karɓi tubansu.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Banu Isra'ila Littafin Attaura bayan ya kuɓutar da su daga Fir'auna da jama'arsa. Babbar hikimar yin haka shi ne domin su kafa al'umma mai bin shari'ar Allah, su zamanto suna da wani saƙo da za su rayu a kansa su kuma yi aiki da shi.

7. Kyakkyawan abu ne ƙwarai ga mai kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riƙa amafani da salo na laluma da lallashi don jan hankulan mutane su saurari maganarsa su karɓi gaskiya daga gare shi.

8. Wajabcin tuba zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) nan take bayan aikata laifi.

9. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana karɓar tuban bayinsa komai girman laifinsu idan har sun tuba sun bar shi.

10. Tuna wa wanda ya yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) laifi ni'imomin da ya yi masa don ya ƙara fahimtar munin laifinsa na yi wa Allah butulci.

Suratul Baƙara (51-54)

وَإِذۡ وَٰعَدۡنَا مُوسَىٰٓ أَرۡبَعِينَ لَيۡلَةٗ ثُمَّ ٱتَّخَذۡتُمُ ٱلۡعِجۡلَ مِنۢ بَعۡدِهِۦ وَأَنتُمۡ ظَٰلِمُونَ ٥١ ثُمَّ عَفَوۡنَا عَنكُم مِّنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٥٢
وَإِذۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡفُرۡقَانَ لَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ٥٣ وَإِذۡ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوۡمِهِۦ يَٰقَوۡمِ إِنَّكُمۡ ظَلَمۡتُمۡ أَنفُسَكُم بِٱتِّخَاذِكُمُ ٱلۡعِجۡلَ
فَتُوبُوٓاْ إِلَىٰ بَارِئِكُمۡ فَٱقۡتُلُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ عِندَ بَارِئِكُمۡ فَتَابَ عَلَيۡكُمۡۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ٥٤

51. Kuma ku tuna lokacin da Muka yi wa Musa wa'adin (ganawa da shi) na kwana arba'in, sannan ku kuma kuka kama bautar ɗan maraƙi a bayansa, alhalin kuna masu zaluntar kawunanku.

52. Sannan sai Muka yi muku afuwa bayan haka, don ku yi godiya.

53. Kuma ku tuna lokacin da Muka ba wa Musa Littafin (Attaura) da abin da yake rarrabewa (tsakanin gaskiya da ƙarya) don ku shiriya.

54. Kuma ku tuna lokacin da Musa ya cewa mutanensa: “Ya ku mutanena, lalle ku kun zalunci kawunanku ta hanyar mayar da ɗan maraƙi abin bauta, don haka ku tuba zuwa ga Mahaliccinku, kuma ku kashe kawunanku; wannan shi ne ya fi alheri a gare ku a wajen Mahaliccinku. Lalle shi Mai yawan karɓar tuba ne, Mai yawan jin ƙai.”

Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tuna musu lokacin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya je ganawa da shi ta tsawon kwana arba’in, su kuma Banu Isra’ila bayan tafiyarsa suka riƙa bauta wa ɗan maraƙi, suka zalunci kansu ta hanyar ɗaukar haƙƙin Allah na bauta su sanya wa ɗan maraƙi. Daga baya da suka tuba sai Allah ya yafe musu ko wataƙila sa yi godiya.
Allah ya faɗi yadda tubar tasu za ta kasance yayin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kirawo su ya shaida musu cewa, sun fa zalunci kansu ta hanyar bautar ɗan maraƙi. Don haka dole ne su tuba; tubar kuwa ita ce, waɗanda ba su yi bautar ba daga cikinsu su kashe waɗanda suka yi, domin ta haka ne kaɗai Allah zai yafe musu laifinsu, don kasancewarsa mai karɓar tuba mai jin ƙai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta raya matattu.

2. Ba wanda zai ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a fili a nan duniya komai matsayinsa.

3. Tsananin taurin kan Banu Isra'ila wanda har ya kai su ga sharɗanta wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) abin da ba mai yiwuwa ba kafin su yi imani da shi.

4. Samun inuwa mai sanyi da abinci mai gina jiki da abin sha mai daɗi, suna daga manya-manyan ni'imomin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Cikar adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka ba ya zaluntar kowa.

Suratul Baƙara (55-57)

وَإِذْ قُلْتُمْ يَٰمُوسَىٰ لَن نُّؤْمِنَ لَكَ حَتَّىٰ نَرَى ٱللَّهَ جَهْرَةً فَأَخَذَتْكُمُ ٱلصَّٰعِقَةُ وَأَنتُمْ تَنظُرُونَ ﴿٥٥﴾ ثُمَّ بَعَثْنَٰكُم مِّنۢ بَعْدِ مَوْتِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿٥٦﴾ وَظَلَّلْنَا عَلَيْكُمُ ٱلْغَمَامَ وَأَنزَلْنَا عَلَيْكُمُ ٱلْمَنَّ وَٱلسَّلْوَىٰ ۖ كُلُوا۟ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقْنَٰكُمْ ۚ وَمَا ظَلَمُونَا وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿٥٧﴾

55. Kuma ku tuna lokacin da kuka ce: “Ya Musa ba za mu yi imani da kai ba har sai mun ga Allah a sarari”, sai tsawa ta halaka ku, alhali kuma kuna kallo.

56. Sannan sai Muka tashe ku bayan mutuwarku, don ku yi godiya.

57. Kuma Muka yi muku inuwa da girgije, kuma Muka saukar muku da *mannu da* (soyayyun) tsuntsayen salwa, ku ci daga daɗaɗan abin da Muka arzuta ku da shi; kuma ba su zalince Mu ba, sai dai kawunansu kaɗai suke zalunta.

A nan har ila yau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tuna musu lokacin da suka faɗa wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, ba za su taɓa yarda da abin da ya zo musu da shi na gaskiya ba har sai ya nuna musu Allah a fili ɓaro-ɓaro sun gan shi. A dalilin haka Allah ya saukar musu da wata tsawa ta riƙa kashe su ɗaya bayan ɗaya suna kallo da idonsu. Sannan bayan duk sun mutu sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tayar da su don su gode masa a kan wannan ni’imar.Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma har wa yau ya tuna musu ni’imar da ya yi musu lokacin da suke yawon ɗimuwa a cikin saharar Sina, ga tsananin zafin rana yana dukan su, sai Allah ya sauko musu da wani girgije ya riƙa yi musu inuwa, sannan ya saukar musu da *Mannu* da *Salwa,* watau darɓa da soyayyun tsuntsayen salwa, ya ce su riƙa cin wannan daddaɗan abinci. To amma duk da irin waɗannan ni’imomi bai sa sun natsu sun gode masa ba, sai ma ƙara butulce masa da suka riƙa yi. To amma wannan duk ba zai cutar da shi da komai ba; kawunansu kaɗai suke cutarwa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimce abubuwa kamar haka:

1. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa wasu daga cikin bayinsa nasara a akan maƙiyansu, to wajibi ne su ƙanƙantar da kansu gare shi, su gode wa ni'imar da ya yi musu ta samun wannan nasarar.

2. Kyautatwa tana jawo ƙaruwar alheri.

3. Kasƙantar da kai da godiya ga Allah suna sanya bawa ya samu gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Canja maganar Allah ta fuskar lafazinta ko ma'anarta mummunan aiki ne kuma babban zalunci ne.

5. Wa'azi da gargaɗi ga masu wasa da maganar Allah da sanya ta inda ba mahallinta ba.

Suratul Baƙara (58-59)

وَإِذْ قُلْنَا ٱدْخُلُواْ هَٰذِهِ ٱلْقَرْيَةَ فَكُلُواْ مِنْهَا حَيْثُ شِئْتُمْ رَغَدًا وَٱدْخُلُواْ ٱلْبَابَ سُجَّدًا وَقُولُواْ حِطَّةٌ نَّغْفِرْ لَكُمْ خَطَٰيَٰكُمْ ۚ وَسَنَزِيدُ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٥٨﴾ فَبَدَّلَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ قَوْلًا غَيْرَ ٱلَّذِى قِيلَ لَهُمْ فَأَنزَلْنَا عَلَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ رِجْزًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُواْ يَفْسُقُونَ ﴿٥٩﴾

58. Kuma ku tuna lokacin da Muka ce: “Ku shiga wannan alƙaryar ku ci daga (kayan marmarinta ta) inda kuka ga dama cikin yalwa, kuma ku shiga ƙofar garin a duƙe, kuma ku ce: “ (Allah Ka) kankare mana laifuffukanmu”, za Mu gafarta muku laifuffukanku. Kuma za Mu ƙara wa masu kyautatawa.

59. Sai waɗanda suka yi zalunci suka canza maganar da aka faɗa musu, sai Muka saukar da wata azaba daga sama a kan waɗanda suka yi zalunci saboda abin da suke aikatawa na fasiƙanci.

A nan Allah yana ci gaba da tuna wa Banu Isra’ila lokacin da ya umarci kakanninsu da cewa, su shiga Baitul Maƙadisi, su ci irin arzikin da Allah ya aje a cikinta a wadace, kuma idan sun zo shiga ta ƙofar garin su sunkuyar da kansu su shiga a duƙe suna neman gafarar Allah. Ya yi musu alƙawarin cewa, idan har sun aikata hakan to zai gafarta musu zunubbansu sannan duk wani wanda ya kyautata aiki daga cikinsu zai ƙara masa falalarsa.
To amma saboda kangarewarsu sai suka canza maganar da aka umarce su da ita, sai suka riƙa cewa: “Kwaya a cikin gashi.” Sannan kuma suka shiga garin suna jan gindi a ƙasa, a dalilin haka ne Allah ya saukar da azabarsa a kansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ne kaɗai mafakar bayinsa yayin da suka shiga cikin wata matsala.

2. Tabbatar da mu'ujiza ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya fitar masa da ruwa mai yawa daga dutse ba tare da wata wahala ba bayan ya doke shi da sandarsa, kuma ya fitar musu da idanuwar ruwa goma sha biyu adadin ƙabilun Banu Isra'ila.

3. Bayanin girmar Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai aikata abin da ya ga dama a sanda ya ga dama.

4. Wata babbar ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Banu Isra'ila a nan shi ne gusar musu da duk wani abu da zai haddasa gaba da husuma a tsakaninsu da samar musu da buƙatarsu ta ruwa ba tare da wata takura ba.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya arzuta bawa ba tare da wata wahala ko wani aiki mai yawa ba.

6. Bayanin cewa Yahudawa wasu mutane ne da suka shahara da ɓarna a bayan ƙasa, shi ya sanya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hane su da ɓarna a nan.

Suratul Baƙara (60)

۞ وَإِذِ ٱسْتَسْقَىٰ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ فَقُلْنَا ٱضْرِب بِّعَصَاكَ ٱلْحَجَرَ ۖ فَٱنفَجَرَتْ مِنْهُ ٱثْنَتَا عَشْرَةَ عَيْنًا ۖ قَدْ عَلِمَ كُلُّ أُنَاسٍ مَّشْرَبَهُمْ ۖ كُلُواْ وَٱشْرَبُواْ مِن رِّزْقِ ٱللَّهِ وَلَا تَعْثَوْاْ فِى ٱلْأَرْضِ مُفْسِدِينَ ﴿٦٠﴾

60. Kuma ka tuna lokacin da Musa ya roƙa wa mutanensa ruwan sha, sai Muka ce: “Ka bugi dutse da sandarka”, sai idanuwan marmaron ruwa goma sha biyu suka ɓuɓbugo daga cikinsa. Haƙiƙa kowaɗanne mutane sun san mashayarsu. (Muka ce): “Ku ci kuma ku sha daga arzikin Allah, kuma kada ku yaɗa ɓarna a bayan ƙasa.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tuna musu lokacin da suka nemi ruwan sha daga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da suka tsinci kansu a saharar Sina, sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙi Allah ya shayar da su ruwa, sai Allah ya umarce shi da ya doki dutse da sandarsa, da ya aikata hakan, nan take kuwa Allah ya fitar musu da idanuwan marmaro na ruwa har guda sha biyu, wato adadin yawan ƙabilar Banu Isra’ila. Kowace ƙabila ta gane mashayarta. Sannan ya umarce su da su ci su sha daga abin da Allah ya arzuta su da shi, kuma kada su kuskura su yaɗa ɓarna a bayan ƙasa. Watau dai Allah ya hore musu ci da sha ba tare da wata wahala ba, kuma ya hore musu ruwan sha isasshe ba tare da wani tirmitsitsi ba.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin wautar Banu Isra'ila da rashin hankalinsu yayin da suka fifita abu mafi ƙasƙanci, watau abincin da ake samu sa ko'ina, a kan abu mafi daraja watau *mannu da* tsintsayen *salwa.*

2. Yahudawa mutane ne da suka shahara da talaucin zuci da tsananin kwaɗayi, kuma komai aka ba su ba sa gamsuwa.

3. Yana daga cikin siffofin Yahudawa ƙetare iyakokin Allah da ta'addanci a kan bayin Allah.

4. Bayanin hatsarin wulaƙanta ni'imar Allah, kuma duk wanda yake aikata haka Allah na iya raba shi da wannan ni'imar da ya ba shi.

5. Halaccin yin tawassuli da addu'ar waɗanda ake sa tsammanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana karɓar addu'arsu, kamar mutanen kirki da iyaye.

6. Duk wani ƙarfi da ɗaukaka na zahiri da Yahudawa za su samu, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, su a wajensa mutane ne ƙasƙantattu wulƙantattu.

Suratul Baƙara (61)

وَإِذْ قُلْتُمْ يَٰمُوسَىٰ لَن نَّصْبِرَ عَلَىٰ طَعَامٍ وَٰحِدٍ فَٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ يُخْرِجْ لَنَا مِمَّا تُنۢبِتُ ٱلْأَرْضُ مِنۢ بَقْلِهَا وَقِثَّآئِهَا وَفُومِهَا وَعَدَسِهَا وَبَصَلِهَا ۖ قَالَ أَتَسْتَبْدِلُونَ ٱلَّذِى هُوَ أَدْنَىٰ بِٱلَّذِى هُوَ خَيْرٌ ۚ ٱهْبِطُوا۟ مِصْرًا فَإِنَّ لَكُم مَّا سَأَلْتُمْ ۗ وَضُرِبَتْ عَلَيْهِمُ ٱلذِّلَّةُ وَٱلْمَسْكَنَةُ وَبَآءُو بِغَضَبٍ مِّنَ ٱللَّهِ ۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقْتُلُونَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ ۚ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَوا۟ وَّكَانُوا۟ يَعْتَدُونَ ﴿٦١﴾

61. Kuma ku tuna lokacin da kuka ce: “Ya Musa, ba za mu iya haƙuri a kan abinci iri ɗaya ba, don haka ka roƙa mana Ubangijinka Ya fitar mana (wani abincin) daga abin da ƙasa take tsirarwa, daga mabunƙusanta da gurjinta da alkamarta da wakenta da albasarta.” Sai ya ce, “Yanzu kwa nemi musanya ƙasƙantaccen abu da wanda yake shi ne mafifici? To ku sauka kowane gari, domin za ku samu abin da kuka roƙa (a cikinsa).” Don haka sai aka sanya musu ƙasƙanci da talauci, kuma suka koma da fushin Allah. Hakan ya faru gare su ne saboda sun kasance suna kafirce wa ayoyin Allah, kuma suna kashe annabawa ba tare da wani haƙƙi ba. Hakan ya faru saboda saɓon da suka yi da kuma ta’addancin da suka riƙa yi.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da tuna musu wata kangarar tasu da butulcewarsu ga ni'imar Allah yayin da suka nuna wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, su fa sun gaji da cin abinci iri ɗaya, (wato *Mannu da Salw*a) wanda Allah yake ba su a kullum ba tare da sun sha wata wahala ba. Don haka suka nemi Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya roƙa musu Ubangijinsa don ya riƙa ba su irin abincin da ƙasa take fitarwa, irin su duma da alkama da albasa da wake da sauransu. A kan haka Annabi Musa ya zarge su da butulci da renuwa, yayin da suka fifita abinci mafi ƙaskanci a kan mafificin abincin da ba inda za a same shi. Don haka ya ce musu, su je su shiga kowane gari za su sami duk abin da suke nema. To ganin yadda suka rena ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu, sai aka jarrabe su da ƙaskanci da talauci wanda zai tilasa su su rusuna wa wasu suna neman taimako a wurinsu tun da sun rena ɗaukakar da Allah ya yi musu. Abu mafi muni ma da ya auka musu shi ne, fushin Allah da suka jawo wa kansu. Kuma Allah ya ce, ya yi musu haka ne saboda bijire wa ayoyinsa da suka yi ta yi, suna kashe annabawansa don sun faɗa musu gaskiya, kuma duk abin da ya kai su ga haka shi ne saɓon Allah da ƙetare iyakokin da suka riƙa yi.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar imani da aiki na ƙwarai. Duk mai wannan siffa zai samu aminci a nan gaba, kuma ba zai yi baƙin cikin abin da ya bari a bayansa ba.

2. Muhimmancin yin bayanin hukuncin Allah ga mabiya wasu addinai da ba Musulunci ba.

3. Yahudawa da Nasara da Sabi'awa waɗanda suka yi imani da Kaɗaitakar Allah, suka yi aiki da shari'un annabawansu, har suka mutu a kan haka kafin aiko Annabi Muhammadu (ﷺ), ko kuma waɗanda suka riski Musulunci daga cikinsu suka musulunta suka bar addininsu na farko, to duk waɗannan sun tsira sun kuma rabauta.

Suratul baqara (62)

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ هَادُواْ وَٱلنَّصَٰرَىٰ وَٱلصَّٰبِـِٔينَ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْأَخِرِ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَلَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٦٢﴾

62. Lalle waɗanda suka yi imani da Yahudawa da Nasara da Sabi'awa, duk wanda ya yi imani da Allah da ranar Lahira kuma ya yi aiki na ƙwarai, to suna da ladansu a wurin Ubangijinsu, kuma babu tsoro a tare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

Hikimar kawo wannan ayar ana tsaka da bayanin laifuffukan Banu Isra'ila ita ce, don a nuna musu cewa, ƙofar tuba gare su a buɗe take matuƙar za su tuba su inganta imaninsu da ranar lahira su yi kyakkyawan aiki, to Allah zai ba su ladansu cikakke kuma babu wani tsoro a tare da su game da abin da za su je lahira su iske, kuma babu wani baƙin ciki da za su yi na abin da suka tafi suka bar shi a nan duniya.
Waɗanda suka yi imani, a nan ana nufin al'ummar Annabi Muhammadu (ﷺ) wadda ta yi imani da shi, ta yi imani da dukkan littattafan Allah da manzanninsa. An ware su da wannan suna domin ƙarfin imaninsu da cikarsa.
Yahudawa kuwa ana nufin mabiya Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka yi imani da shi, suka yi aiki da abin da aka saukar masa kafin a shafe aiki da addininsa, ko kuma kafin su gurɓata shi.

Nasara kuma, ana nufin mabiya Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kafin a shafe addininsa ko kafin su jirkita shi.
Sabi'awa kuwa wasu kungiyoyi ne, daga cikinsu akwai waɗanda suka kasance a kan aƙidar kaɗaita Allah da haramta duk wata alfasha da zalunci, duk da kasancewarsu ba bisa wani addini suke ba, to amma ba sa aikata kafirci. To duk wanda ya kyautata aiki daga cikin waɗannan al'ummomi da suka gabata, yana da kyakkyawan sakamako a wurin Allah, ba zai ɓata masa rayuwarsa ta lahira ba.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin ƙarfin Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da cikar ikonsa ta yadda ya tunɓuke dotse daga inda yake, ya ɗaga shi sama ya bar shi yana reto ba tare da wani abu ya riƙe shi ba.

2. Wajabcin riƙo da addini da ƙarfi a koyaushe.

3. Mummunan halin Banu Isra'ila na taurin kai da rashin wa'azantuwa da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Haramcin bin wasu dabaru don kyauce wa hukunci shari'ar Allah da aikata haramun.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayar da labaran waɗanda suka gabata domin wa'azantarwa.

6. Babu masu wa'azantuwa da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sai masu taƙawa kaɗai.

Suratul Baƙara (63-66)

وَإِذْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَكُمْ وَرَفَعْنَا فَوْقَكُمُ ٱلطُّورَ خُذُواْ مَآ ءَاتَيْنَٰكُم بِقُوَّةٍ وَٱذْكُرُواْ مَا فِيهِ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿٦٣﴾ ثُمَّ تَوَلَّيْتُم مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ ۖ
فَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ لَكُنتُم مِّنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴿٦٤﴾ وَلَقَدْ عَلِمْتُمُ ٱلَّذِينَ ٱعْتَدَوْاْ مِنكُمْ فِى ٱلسَّبْتِ فَقُلْنَا لَهُمْ كُونُواْ قِرَدَةً
خَٰسِـِٔينَ ﴿٦٥﴾ فَجَعَلْنَٰهَا نَكَٰلًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهَا وَمَا خَلْفَهَا وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴿٦٦﴾

63. Kuma ku tuna lokacin da Muka ɗauki alƙawari mai ƙarfi daga gare ku, kuma Muka ɗaga dusten Ɗuri a kanku (Muka ce): "Ku karɓi abin da Muka ba ku da ƙarfi (Attaura), kuma ku tuna abin da yake cikinsa, don ku yi taƙawa."

64. Sannan bayan haka sai kuka juya da baya, to ba domin falalar Allah da rahamarsa a gare ku ba, lalle da kun kasance daga cikin asararru.

65. Kuma haƙiƙa kun san waɗanda suka yi shisshigi daga cikinku game da ranar Assabar, sai Muka ce da su: "Ku zama birrai kuna ƙaskantattu."

66. Sai Muka sanya ta (wannan uƙubar) ta zama izina ga al'ummomin da suke zamanin faruwarta da kuma garuruwan da suke daura da su, kuma don ta zama wa'azi ga masu taƙawa.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da tunatar da Banu Isra'ila alƙawarin da ya yi da su na cewa, za su yi imani da Manzansa (ﷺ); za su riƙe shari'arsa, kuma za su ƙanƙame Attaura da gaske, har ma sai da ya ɗaga dutsen Ɗuri a samansu don su karɓi wannan alƙawari da ya yi da su, su ci gaba da karanta Attaura suna aiki da abin da yake cikinta na ilmantarwa don su zama masu taƙawa. Amma kuma

daga bisani sai suka warware wannan alƙawari, suka bijire masa. Ba don Allah ya nufe su da falalarsa, ya ba su damar tuba kuma ya karɓi tubarsu ba, to da sun wayi gari cikin halakakku a duniya da lahira. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da su labarin wasu kangararru daga cikinsu waɗanda suka kangare wa dokar Allah wadda ta hana su kamun kifi a duk ranar Assabar, ya neme su da su zauna gidajensu, amma sai suka bijire ma wannan dokar, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da su birai, ya ƙaskanta su. Kuma Allah ya sanya wannan uƙuba da ya yi musu ta zama abin tsoratarwa kuma wa'azi da izina ga masu laifuka irin nasu, har ma da garuruwan da suke maƙotaka da su, hakanan kuma ta zama tunatarwa ga masu taƙawa.

A wannan ƙissa za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Taurin kan Banu Isra'ila da rashin ladabinsu ga annabawansu, har ta kai sun tuhumi Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da yi musu izgili ko cewa, ya yi wa Allah ƙarya ya jingina masa abin da bai faɗa ba ya ce ya faɗi.

2. Girman kan Banu Isra'ila da rashin karɓar umarnin Allah a karon farko, sai bayan an sha daga da su. Kuma dubi yadda suka kasa cewa: 'Ka roƙa mana Allah", sai dai su ce: "Ka roƙa mana Ubangijinka." Me zai hana su su ce: "Ubangijinmu"? Ba komai wannan yake nunawa ba, sai girman kai da nuna tawaye.

3. Tambayar ƙwaƙwa marar amfani tana iya sa a faɗa cikin tsanani. Domin tun farko da sun yanka kowace irin saniya, da ta gamsar, to amma sai suka tsananta tambaya, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tsananta musu.

4. Yi wa mutane izgili yana daga cikin ɗabi'a ta wawayen mutane marasa tunani, shi ya sa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nemi Allah ya kiyaye shi daga faɗawa cikin wannan ɗabi'a.

5. Sandararrun halittu na Allah, kamar duwatsu da makamantansu, duk suna jin tsoron Allah, saboda sun san girmansa da ɗaukakarsa.

Suratul Baƙara (67-74)

وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَأْمُرُكُمْ أَن تَذْبَحُوا۟ بَقَرَةً ۖ قَالُوٓا۟ أَتَتَّخِذُنَا هُزُوًا ۖ قَالَ أَعُوذُ بِٱللَّهِ أَنْ أَكُونَ مِنَ ٱلْجَٰهِلِينَ ﴿٦٧﴾ قَالُوا۟ ٱدْعُ لَنَا
رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا هِىَ ۚ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٌ لَّا فَارِضٌ وَلَا بِكْرٌ عَوَانٌۢ بَيْنَ ذَٰلِكَ ۖ فَٱفْعَلُوا۟ مَا تُؤْمَرُونَ ﴿٦٨﴾ قَالُوا۟ ٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا
مَا لَوْنُهَا ۚ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٌ صَفْرَآءُ فَاقِعٌ لَّوْنُهَا تَسُرُّ ٱلنَّٰظِرِينَ ﴿٦٩﴾ قَالُوا۟ ٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا هِىَ إِنَّ ٱلْبَقَرَ تَشَٰبَهَ عَلَيْنَا وَإِنَّآ إِن
شَآءَ ٱللَّهُ لَمُهْتَدُونَ ﴿٧٠﴾ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٌ لَّا ذَلُولٌ تُثِيرُ ٱلْأَرْضَ وَلَا تَسْقِى ٱلْحَرْثَ مُسَلَّمَةٌ لَّا شِيَةَ فِيهَا ۚ قَالُوا۟ ٱلْـَٰٔنَ جِئْتَ بِٱلْحَقِّ ۚ
فَذَبَحُوهَا وَمَا كَادُوا۟ يَفْعَلُونَ ﴿٧١﴾ وَإِذْ قَتَلْتُمْ نَفْسًا فَٱدَّٰرَـْٔتُمْ فِيهَا ۖ وَٱللَّهُ مُخْرِجٌ مَّا كُنتُمْ تَكْتُمُونَ ﴿٧٢﴾ فَقُلْنَا ٱضْرِبُوهُ بِبَعْضِهَا ۚ كَذَٰلِكَ يُحْىِ ٱللَّهُ
ٱلْمَوْتَىٰ وَيُرِيكُمْ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿٧٣﴾ ثُمَّ قَسَتْ قُلُوبُكُم مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ فَهِىَ كَٱلْحِجَارَةِ أَوْ أَشَدُّ قَسْوَةً ۚ وَإِنَّ مِنَ ٱلْحِجَارَةِ لَمَا
يَتَفَجَّرُ مِنْهُ ٱلْأَنْهَٰرُ ۚ وَإِنَّ مِنْهَا لَمَا يَشَّقَّقُ فَيَخْرُجُ مِنْهُ ٱلْمَآءُ ۚ وَإِنَّ مِنْهَا لَمَا يَهْبِطُ مِنْ خَشْيَةِ ٱللَّهِ ۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿٧٤﴾

67. Kuma ku tuna lokacin da Musa ya ce wa mutanensa: "Allah Yana umartar ku da ku yanka saniya", sai suka ce: "Yanzu ka riƙa yi mana izgili?" Sai ya ce: "Ina neman Allah Ya kiyaye ni da in zama cikin jahilai!"

68. Sai suka ce: “Ka roƙa mana Ubangijinka Ya yi mana bayanin yaya take?” Sai ya ce: “Lalle Shi yana cewa, lalle ita saniya ce, ba tsohuwa ba kuma ba budurwa ba, tana tsakatsakin haka.” Don haka ku aikata abin da ake umartar ku.

69. Sai suka ce: “Ka roƙa mana Ubangijinka Ya bayyana mana mene ne launinta?” Sai ya ce, “Lalle Shi yana cewa, lalle ita saniya ce mai launin fatsi-fatsi mai tsananin cizawa, tana faranta wa masu kallon ta rai.”

70. Sai suka ce: “Ka roƙa mana Ubangijinka Ya bayyana mana yaya take, lalle shanu sun rikitar da mu, kuma lalle mu in Allah Ya so masu shiryuwa ne.”

71. Ya ce: “Lalle Shi Yana cewa, ita saniya ce wadda ba horarriya ba ce da take noma kasa, kuma ba ta shayar da shuka; lafiyayya ce, babu dabbare-dabbare a jikinta”. Sai suka ce: “Yanzu ne ka zo da gaskiya”. Sai suka yanka ta, kamar dai ba za su aikata ba.

72. Kuma ku tuna lokacin da kuka kashe wani mutum, kuma kuka riƙa tura wa juna (laifin kisan), Allah kuma Mai bayyanar da abin da kuka kasance kuna ɓoyewa ne.

73. Sai Muka ce: “Ku doke shi (mataccen) da wani sashinta (saniyar).” Kamar haka ne Allah Yake raya matattu, Yake kuma nuna muku ayoyinsa don ku hankalta.

74. Sannan sai zukatanku suka ƙeƙashe bayan haka, suka zama kamar dutse ko ma fiye da dutse ƙeƙashewa. Kuma lalle daga cikin duwatsu akwai waɗanda ƙoramu suke ɓuɓɓugowa daga cikinsu; akwai kuma waɗanda suke tsatssagewa ruwa ya fito daga cikinsu; akwai kuma waɗanda suke faɗowa saboda tsoron Allah. Allah ba marafkani ne ba game da abin da kuke aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da Banu Isra’ila labarin iyayensu da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da suka neme shi da ya taimaka musu da binciken gano wani daga cikinsu da ya yi kisan kai, kuma ba su gane kowane ne shi ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa wahayi da ya umarce su da su yanka saniya, domin su doki wannan mamaci da wani ɓangare daga jikinta, sai ya dawo da ransa ya faɗa musu wanda ya kashe shi. To amma Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai bayyana musu wasu siffofi takamaimai na saniyar ba, domin yana nufin kowace iri suka yanka ta gamsar. To amma saboda tsaurin kansu da ta’annutinsu, sai suka ɗauki maganar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a matsayin izgili yake yi musu. Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nemi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsare shi daga kasancewa cikin wawayen mutane masu yi wa mutane izgili. Duk da haka wannan bai sa Banu Isra’ila sun yanka saniyar ba, sai suka ci gaba da yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) tambayar ƙwaƙwa, suka ce ya roƙi Ubangijinsa ya faɗa musu wace irin saniya za su yanka? Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya faɗa musu cewa, Allah ya ce saniyar da za su yanka ba tsohuwa ba ce, kuma ba yarinya ba ce; saniya ce wadda take tsakatsaki, ba babba ba sosai, ba kuma ƙarama sosai ba. To duk da haka ba su wadatu sun tsaya iya nan ba, sai suka ƙara zaƙulo wata tambayar suka ce, Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tambayo musu Ubangijinsa launin saniyar da za su yanka. Annabi Musa ya ce, Allah ya faɗa masa cewa saniya ce mai rawayar launi tsantsa, kuma kyakkyawa wadda kyanta yake faranta wa duk wanda ya kalle ta rai.
To maimakon Banu Isra’il su tsaya iya nan da tambayoyinsu na ƙwaƙwa, sai suka ci gaba da ce wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su fa shanu sun rikita su, har sun kasa gano wacce ake so su

yanka, don haka Annabi Musa ya sake neman Ubangijinsa da ya ƙara fayyace masa irin saniyar da yake nufi. To amma a wannan karo, sai suka ce insha Allahu za su gano saniyar da ake musu bayani. Daga nan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sake faɗa musu cewa, Allah ya faɗa masa cewa saniyar da ba a taɓa sa ta wani aiki ba na noma ko na ban ruwa ba, sannan kuma ba ta da wata naƙasa a tare da ita, kamar yadda kuma launin nata na rawaya ne tsantsa, ba tare da ya gauraya da wani launi ba. To fa sai a nan ne suka ce wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), yanzu suka ji ya zo da batu na gaskiya wajen tantance musu siffofin saniyar. Sai suka tafi neman ta, har suka samo ta suka yanka ta, abin da kamar ma ba za su iya yi ba. Wato sun yanka ta ba da son ransu ba. Ko kuma saboda irin yadda suka riƙa tambayar ƙwaƙwa, har sun kusa su ce ma sun fasa yanka saniyar. Domin da suna da sha'awar zartar da umarnin da Allah ya yi musu, da a karon farko sun zartar, to amma sai suka tsaya tambayoyi na rashin yarda, suka tsananta, sai su ma Allah ya tsananta musu. Daga nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su doki wannan mamaci da wani ɓangare na saniyar, sai suka yi hakan, Allah kuma ya sake raya shi, ya tashi ya faɗa musu sunan wanda ya kashe shi.
Wannan abu da ya faru yana cikin dalilai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Banu Isra'ila da sauran 'yan'adam cewa, Allah zai iya sake tayar da matattu don yi musu hisabi a ranar gobe ƙiyama. Allah ya ce ya yi musu haka ne don su yi hankali, su bar aikata duk wani abu wanda zai cutar da su a wurin Allah. To amma maimakon su yi hankali su ƙara nutsuwa, sai zukatansu suka bushe, suka ƙeƙashe, suka zama masu tauri kamar dutse, ko ma fiye da dutse, domin dutse duk da taurinsa, ya fi zukatan Yahudawa laushi, domin a cikin duwatsu akwai waɗanda ruwa yake kwarara daga cikinsu, akwai kuma wanda yake tsagewa yana fitar da ruwa, akwai kuma wanda yake faɗowa ƙasa saboda tsoron Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙara tsoratar da su ta hanyar faɗa musu cewa yana sane da duk abin da suke kitsawa na saɓon Allah, kuma sai ya yi musu cikakkiyar sakayya a kan aikinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana lallashin Annabinsa (ﷺ) da nuna masa kada ya damu da irin halin Yahudu, saboda su mutane ne masu taurin kai, zai yi wahala su yi imani.

2. Canza ma'anonin ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bayan fahintarsu ya fi matuƙar muni, fiye da wanda zai canza ma'anar saboda rashin fahinta, domin jahili ana iya yi masa uzuri da jahilcinsa, saɓanin wanda ya sani amma ya karkace.

3. Ya kamata ga mutum ya zama mai lura da hankaltar abubuwa, ya zama yana tunani game da duk abin da zai aikata, ko zai faɗa, kafin ya kai ga aikatawa ko ya faɗa.

4. Abu ne mai matuƙar muni mutum ya zauna ba tare da yana fahintar littafin Allah ba, sai dai bibiyar tatsuniyoyi da maganganu marasa tushe, ko kuma ya zama mai karatun littafin Allah, amma ba tare da neman sanin ma'anoninsa ba, sai tilawarsa kaɗai.

5. Imani da fatar baki kaɗai ba zai shigar da mutum Aljanna ba, sai idan ya haɗa da ƙudurin zuciya da ayyuka na ƙwarai, wannan shi ne ya sa munafuƙai ba za su shiga Aljanna ba.

6. Yana daga cikin miyagun ɗabi'u na Yahudawa, ƙarya da ha'inci da yin baki-biyu.

7. Yana daga cikin siffofin Allah, kasancewarsa mai gaskiya kuma ba mai saɓa alƙawari ba. Wannan yana nuna cikar ikonsa da kuma cikakkiyar gaskiyarsa. Saboda gazawa, ko kuma ƙarya suna daga cikin dalilan saɓa alƙawari. Allah kuwa ya tsarkaka daga gare su.

Suratul Baƙara (75-82)

۞ أَفَتَطۡمَعُونَ أَن يُؤۡمِنُواْ لَكُمۡ وَقَدۡ كَانَ فَرِيقٞ مِّنۡهُمۡ يَسۡمَعُونَ كَلَٰمَ ٱللَّهِ ثُمَّ يُحَرِّفُونَهُۥ مِنۢ بَعۡدِ مَا عَقَلُوهُ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ٧٥ وَإِذَا لَقُواْ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَا بَعۡضُهُمۡ إِلَىٰ بَعۡضٖ قَالُوٓاْ أَتُحَدِّثُونَهُم بِمَا فَتَحَ ٱللَّهُ عَلَيۡكُمۡ لِيُحَآجُّوكُم بِهِۦ عِندَ رَبِّكُمۡۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٧٦ أَوَلَا يَعۡلَمُونَ أَنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعۡلِنُونَ ٧٧ وَمِنۡهُمۡ أُمِّيُّونَ لَا يَعۡلَمُونَ ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّآ أَمَانِيَّ وَإِنۡ هُمۡ إِلَّا يَظُنُّونَ ٧٨ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ يَكۡتُبُونَ ٱلۡكِتَٰبَ بِأَيۡدِيهِمۡ ثُمَّ يَقُولُونَ هَٰذَا مِنۡ عِندِ ٱللَّهِ لِيَشۡتَرُواْ بِهِۦ ثَمَنٗا قَلِيلٗاۖ فَوَيۡلٞ لَّهُم مِّمَّا كَتَبَتۡ أَيۡدِيهِمۡ وَوَيۡلٞ لَّهُم مِّمَّا يَكۡسِبُونَ ٧٩ وَقَالُواْ لَن تَمَسَّنَا ٱلنَّارُ إِلَّآ أَيَّامٗا مَّعۡدُودَةٗۚ قُلۡ أَتَّخَذۡتُمۡ عِندَ ٱللَّهِ عَهۡدٗا فَلَن يُخۡلِفَ ٱللَّهُ عَهۡدَهُۥٓۖ أَمۡ تَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٨٠ بَلَىٰۚ مَن كَسَبَ سَيِّـَٔةٗ وَأَحَٰطَتۡ بِهِۦ خَطِيٓـَٔتُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٨١ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٨٢

75. Yanzu (ku muminai) kwa sa ran su yi imani saboda ku, alhalin wata ƙungiya daga cikinsu suna sauraron maganar Allah sannan su jirkita ta bayan sun fahimce ta alhalin kuwa suna sane?

76. Kuma idan suka haɗu da waɗanda suka yi imani sai su ce: “Mun yi imani”, amma kuma idan sashinsu ya keɓance da sashi sai su ce: “Yanzu kwa riƙa faɗa musu abin da Allah Ya yi muku buɗi da shi don su kafa muku hujja da shi a wurin Ubangijinku? Shin ba za ku hankalta ba?”

77. Shin ko ba su san Allah Yana sane da abin da suke ɓoyewa da abin da suke bayyanawa ba?

78. Kuma daga cikinsu akwai jahilai waɗanda ba su san Littafi ba sai burace-burace, kuma zato kawai suke yi.

79. To tsananin azaba ya tabbata ga waɗanda suke rubuta littafi da hannayensu sannan su ce: “Wannan daga Allah yake”, don su musanya shi da wani ɗan kuɗi kaɗan. To tsananin azaba ya tabbata a gare su saboda abin da hannayensu suka rubuta, kuma tsananin azaba ya tabbata a gare su saboda abin da suka kasance suna tsuwurwuta.

80. Kuma suka ce: “Wuta ba za ta shafe mu ba sai cikin wasu 'yan kwanaki ƙididdigaggu.” Ka ce: “Shin kun yi wani alƙawari ne da Allah, don haka Allah ba zai saba alƙawarinsa ba? Ko kuma kuna faɗar abin da ba ku da ilimi ne kuna jingina wa Allah?”

81. E! Wanda duk ya aikata mummunan aiki kuma laifuffukansa suka kewaye shi, to waɗannan su ne ‘yan wuta, su masu dawwama ne a cikinta.

82. Waɗanda kuma suka yi imani kuma suka yi ayyuka na ƙwarai, to waɗannan 'yan Aljanna ne, kuma su masu dawwama ne a cikinta.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin yanayin da zukatan Banu Isra’ila suka zama, yadda suka taurare kamar duwatsu ko ma fiye da duwatsu, sai ya dawo kan muminai a waɗannan ayoyi yana faɗa musu cewa, su fitar da rai game da imanin waɗannan mutane, domin babu wata alama da ta nuna suna shirye da karɓar shiriya. Hasali ma malamansu ma waɗanda suke karanta musu Attaura da abin da yake cikinta na maganar Allah, suna canja ta, suna gurɓata ta, bayan kuwa sun fahimce ta, sai suka canza ma’anoninta zuwa wata ma’ana daban da za ta yi daidai da son ransu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗi mummunan hali na wasu Yahudawa, waɗanda suka yafa rigar munafinci a jikinsu. Wato duk lokacin da suka haɗu da Annabi (ﷺ) da sahabbansa, sai su ce: “Ai mu muminai ne”, amma idan sun koma cikin ‘yan uwansu Yahudu, sai sauran Yahudawan da ba su yafa rigar munafinci ba, su riƙa zargin waɗancan munafuƙan Yahudawan, suna ce musu: “Me ya sa za ku riƙa faɗa wa Musulmi abin da Allah ya sanar da mu a Attaura na siffofin Annabi ko labarin irin azabar da Allah ya saukar wa kakanninmu saboda kangararsu ko kuma abin da ya sanar da mu na cewa, akwai Annabin da zai bayyana mai siffofi iri kaza da kaza? Domin fa yin haka ai wata hujja ce kuke ba su da za su kafa mana ita gobe ƙiyama a gaban Allah cewa mun san gaskiya, kawai mun ƙi yin imani ne da gangan. Wannan abu da kuke yi rashin hankali ne.” Sai Allah ya ce, Yahudawa suna irin waɗannan maganganu da ‘yan uwansu a ɓoye, kamar ba su san Allah ya san duk abin da suke bayyanawa da abin da suke ɓoyewa ba, shi a wurinsa babu wani bambanci tsakanin abin da suke bayyanawa, da abin da suke ɓoyewa a zukatansu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Yahudawa ba dukansu ne suke da ilimi ba; a cikinsu akwai ma waɗanda ba su iya ko rubutu da karatu ba, don haka ba ma sa iya karanta littafin Attaura; abin da kawai suka sani shi ne tatsuniyoyi da shaci-faɗi, kamar ganin da suke yi cewa babu wanda zai shiga Aljanna sai su, ko su ba za a sa su a wuta ba sai na ‘yan kwanaki kaɗan, da ire-iren waɗannan tatsuniyoyi marasa kan-gado. Allah ya ce babu komai na ilimi a tare da irin waɗannan Yahudawa in ban da zato da kame-kame. Kamar yadda ya faɗa a Suratun Nisa’i, aya ta 157.
Sannan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani kason na Yahudawa, waɗanda su ne miyagun malamansu, waɗanda babu Allah a zukatansu sai neman abin duniya kawai, don haka sai su riƙa canza littafin Attaura, suna kuma rubuta wasu ƙarairayi da hannuwansu, amma sai su ce maganar Allah ce. To waɗannan miyagun malaman za su gamu da azaba mai tsanani saboda ƙaryar da suka riƙa yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) domin su ci haram da ita, don haka sakamakonsu mai muni ne ƙwarai da gaske a lahira.
Daga nan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci aƙidar da ta ja waɗannan miyagun malaman suka riƙa yi wa Allah ƙarya don su ci dukiyar mabiyansu, ta cewa, wai wuta a lahira ba za ta ci su ba sai cikin wasu ‘yan kwanaki kaɗan, daga nan sai a fitar da su, don haka ba su da wata babbar matsala a lahira komai suka aikata a nan duniya. Sai Allah ya umarci Annabi (ﷺ) da ya mayar musu da martani, ya tambaye su, ko suna da wata yarjejeniya da suka yi tsakaninsu da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a kan hakan, wadda za ta tabbatar da abin da suke da’awa? Idan suna da ita, to shi ke nan suna da hujja a hannunsu, domin Allah ba ya karya alƙawari. Idan kuwa babu wannan yarjejeniyar, to saboda me za su riƙa faɗar ƙarya suna jingina wa Allah?
Sannan sai Allah ya ƙaryata waccan magana tasu ta cewa, su ba za a sanya su a wuta ba, sai na wanin ɗan taƙaitaccen lokaci, ya ce, ba haka ne ba, hukuncin Allah shi ne, duk wanda ya aikata laifi, kamar irin haɗa Allah da wani ko yi masa ƙarya, har zunubansa suka dabaibaye shi ta ko’ina, ya kuma mutu a kai bai tuba ba, to zai shiga wuta ne ya kuma zauna cikinta har abada babu fita. Su kuma waɗanda suka ba da gaskiya da Allah, suka yi kyawawan ayyuka, to waɗannan ‘yan Aljanna ne masu zama a cikinta har abada babu fita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman haƙƙin iyaye, sannan haƙƙin da yake bi masa shi ne haƙƙin dangi da ‘yan’uwa na kusa, sannan haƙƙin maraya, wanda saboda ƙanƙantarsa da tsananin buƙatarsa ga wanda zai kula shi, shi ne ya sa aka fara ambaton sa kafin a ambaci mabuƙaci, saboda shi mabuƙaci babba ne, zai iya kula da kansa ta hanyar aikin ƙarfi, saɓanin maraya.

2. Duk wata al’umma da addini ɗaya ya haɗa ta, to tamkar jiki guda ne, shi ya sa a nan Allah ya ce: “Kada ku riƙa zubar da jininku, kuma kada ku riƙa fitar da kawunanku daga gidajenku.”

3. Ba ya halatta ga muminai su ƙulla yarjejeniya da wasu wadda ta ƙunshi warware yarjejeniyarsu da Allah ko ta ci karo da wata maslaha ta al'ummar Musulmi da sunan kare kai ko haɓaka tattalin arziki.

Suratul Baƙara (83-86)

وَإِذْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَ بَنِيٓ إِسْرَٰٓءِيلَ لَا تَعْبُدُونَ إِلَّا ٱللَّهَ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَانًا وَذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَقُولُوا۟ لِلنَّاسِ حُسْنًا وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ثُمَّ تَوَلَّيْتُمْ إِلَّا قَلِيلًا مِّنكُمْ وَأَنتُم مُّعْرِضُونَ﴿٨٣﴾ وَإِذْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَكُمْ لَا تَسْفِكُونَ دِمَآءَكُمْ وَلَا تُخْرِجُونَ أَنفُسَكُم مِّن دِيَٰرِكُمْ ثُمَّ أَقْرَرْتُمْ وَأَنتُمْ تَشْهَدُونَ﴿٨٤﴾ ثُمَّ أَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ تَقْتُلُونَ أَنفُسَكُمْ وَتُخْرِجُونَ فَرِيقًا مِّنكُم مِّن دِيَٰرِهِمْ تَظَٰهَرُونَ عَلَيْهِم بِٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِ وَإِن يَأْتُوكُمْ أُسَٰرَىٰ تُفَٰدُوهُمْ وَهُوَ مُحَرَّمٌ عَلَيْكُمْ إِخْرَاجُهُمْ ۚ أَفَتُؤْمِنُونَ بِبَعْضِ ٱلْكِتَٰبِ وَتَكْفُرُونَ بِبَعْضٍ ۚ فَمَا جَزَآءُ مَن يَفْعَلُ ذَٰلِكَ مِنكُمْ إِلَّا خِزْىٌ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ وَيَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يُرَدُّونَ إِلَىٰٓ أَشَدِّ ٱلْعَذَابِ ۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ﴿٨٥﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱشْتَرَوُا۟ ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا بِٱلْءَاخِرَةِ ۖ فَلَا يُخَفَّفُ عَنْهُمُ ٱلْعَذَابُ وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ﴿٨٦﴾

83. Kuma ka tuna lokacin da Muka ɗauki alƙwari daga Banu Isra'ila cewa, ba za ku bauta wa kowa ba sai Allah, kuma za ku kyautata wa iyaye da makusanta da marayu da miskinai, kuma ku riƙa yi wa mutane kyakkyawar magana, kuma ku tsai da salla, kuma ku ba da zakka, sannan sai kuka ba da baya sai 'yan kaɗan daga cikinku, alhalin kuna masu bijirewa.

84. Kuma ku tuna lokacin da muka ɗauki alƙawari da ku cewa, ba za ku zubar da jinanenku ba, kuma ba za ku fitar da junanku daga gidajenku ba, sannan kuka tabbatar da hakan, alhalin kuna masu shaida.

85. Sannan sai ga ku, ku ɗin nan kuna kashe junanku, kuma kuna fitar da wata ƙungiya daga cikinku daga gidajensu, kuma kuna taimaka wa juna wajen cutar da su ta hanyar laifi da zalunci. Idan kuma sun zo muku suna kamammun yaƙi sai ku fanshe su, alhali fitar da su haramun ne a gare ku. Yanzu kwa riƙa yin imani da sashen Littafi kuma ku riƙa kafircewa da wani sashen? To ba komai ne sakamakon wanda yake aikata haka daga cikinku ba face wani wulaƙanci a rayuwar duniya, kuma ranar alƙiyama a mayar da su zuwa ga mafi tsananin azaba, kuma Allah ba rafkananne ba ne game da abin da kuke aikatawa.
86. Waɗannan su ne waɗanda suka musanya rayuwar duniya da ta lahira, kuma ba za a sassauta musu azaba ba, kuma ba za a taimaka musu ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tuna wa Banu Isra'ila wani ƙaƙƙarfan alƙawari da ya yi da su na cewa, kada su bauta wa kowa sai shi kaɗai, ba tare da sun yi shirka da komai ba, kuma su kyautata wa iyayensu ta duk hanyoyin kyautatawa, hakanan su taimaka wa marayu, wato yaran da suka rasa iyayensu maza kuma ba su balaga ba, mazansu da matansu. Sannan ya umarce su da su zamo masu faɗa wa mutane maganganu masu daɗi, wanda hakan ya ƙunshi yi musu nasiha da wa'azi ta hanyar da ta dace, ya ƙunshi yafiya da afuwa da sauransu. Kamar yadda ya umarce su da su tsayar da salla tare da kula da hukunce-hukuncenta, su kuma fitar da zakkar dukiyoyinsu su ba wa talakawa. To amma duk bayan wannan alƙawari mai ƙarfi da ya yi da su, sai ya zamana 'yan kaɗan ne daga cikinsu suka cika wannan alƙawari.
Bayan wancan alƙawarin, ya sake tuna musu wani alƙawarin na daban da ya yi da su, wanda shi ne ya hana su su riƙa kashe junansu ko kuma wasu daga cikinsu su riƙa korar wasu daga gidajensu haka kawai, ba tare da wani laifi ba, kuma suka amince da wannan alƙawari, suka ba da shaida a kansa, ba su musa ba ko kaɗan. To amma kuma sai ga shi daga baya sun zo suna faɗa da junansu, har suna kashe juna, wasu daga cikinsu suna korar 'yan uwansu Yahudawa daga gidajensu ba gaira ba dalili, har ta kai ga suna taimaka wa wasu a kan cutar 'yan uwansu, saboda tsabar aikata laifi da ta'addanci irin nasu.

Wata sabuwar kuma ita ce, bayan wannan kashe-kashe da suke yi a junansu da korar junansu daga gidajensu, sai kuma ga shi idan wasu daga cikin ‘yan’uwansu Yahudawa sun faɗa hannayen abokan gabarsu a matsayin fursunonin yaki, sai kuma su zo suna fansar su da dukiyoyinsu, tare da cewa tun farko Allah ya hana su korar ‘yan’uwan nasu daga gidajensu, ya hana su su taimaka wa wasu makiyansa a kan yakar ‘yan’uwansu, amma ba su hanu daga aikata hakan ba. Shi ne a nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake zargin su da irin wannan ɗanyen aikin nasu. Yaya za su ba da gaskiya da wani hukunci na Attaura, wanda shi ne fansar ‘yan’uwansu daga hannayen makiyansu, amma kuma su kafirce wa wasu hukunce-hukuncen, waɗanda su ne hana kashe-kashe a junansu da fitar da juna daga gidajensu?! Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗi sakamakon duk mai aikata irin waɗannan ayyuka da cewa, yana tare da taɓewa a nan duniya, kuma ranar lahira zai gamu da matsananciyar azaba, domin duk irin abin da suke aikatawa Allah yana sane da shi, babu abin da yake ɓuya a gare shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna mana irin waɗannan Yahudawa su ne waɗanda suka yi musanyar rayuwar duniya da ta lahira, a dalilin kafirce wa shari’ar Allah da suka yi, don haka ba za a taba sassauta musu azaba ba ranar gobe ƙiyama, kuma babu wani mai kawo musu ɗauki ya ƙwace su daga azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawan da suka zo daga cikin Banu Isra’ila bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun riƙa aiki ne da shari’arsa.

2. Daga cikin ayyukan mala’iku akwai ƙarfafar manzannin Allah.

3. Asali zukatan ‘yan’adam a buɗe suke, gaskiya na iya shigar su, kafircin ɗan’adam ne yake musabbabin Allah ya la’ance shi, sai ya kulle masa ƙofofin shiriya.

4. Annabta falala ce daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da yake bayar da ita ga wanda ya zaɓa.

Suratul Baƙara (87-90)

وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ وَقَفَّيۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِۦ بِٱلرُّسُلِۖ وَءَاتَيۡنَا عِيسَى ٱبۡنَ مَرۡيَمَ ٱلۡبَيِّنَٰتِ وَأَيَّدۡنَٰهُ بِرُوحِ ٱلۡقُدُسِۗ أَفَكُلَّمَا جَآءَكُمۡ رَسُولُۢ بِمَا لَا تَهۡوَىٰٓ أَنفُسُكُمُ ٱسۡتَكۡبَرۡتُمۡ فَفَرِيقٗا كَذَّبۡتُمۡ وَفَرِيقٗا تَقۡتُلُونَ ٨٧ وَقَالُواْ قُلُوبُنَا غُلۡفُۢۚ بَل لَّعَنَهُمُ ٱللَّهُ بِكُفۡرِهِمۡ فَقَلِيلٗا مَّا يُؤۡمِنُونَ ٨٨ وَلَمَّا جَآءَهُمۡ كِتَٰبٞ مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِ مُصَدِّقٞ لِّمَا مَعَهُمۡ وَكَانُواْ مِن قَبۡلُ يَسۡتَفۡتِحُونَ عَلَى ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَلَمَّا جَآءَهُم مَّا عَرَفُواْ كَفَرُواْ بِهِۦۚ فَلَعۡنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٨٩ بِئۡسَمَا ٱشۡتَرَوۡاْ بِهِۦٓ أَنفُسَهُمۡ أَن يَكۡفُرُواْ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بَغۡيًا أَن يُنَزِّلَ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۖ فَبَآءُو بِغَضَبٍ عَلَىٰ غَضَبٖۚ وَلِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٞ مُّهِينٞ ٩٠

87. Kuma haƙiƙa Mun ba wa Musa Littafi, kuma Muka biyo bayansa da manzanni, kuma Mun bai wa Isa ɗan Maryam hujjoji bayyananu, kuma Mun ƙarfafe shi da Ruhi mai tsarki. Ashe yanzu duk sa'adda wani manzo ya zo muku da abin da zukatanku ba sa so, sai ku yi girman kai, don haka sai ku ƙaryata wasu, kuma ku kashe wasu?

88. Suka ce kuma: “Zukatanmu rufaffu ne.” A’a ba haka ba ne, Allah dai Ya la'ane su ne saboda kafircinsu, don haka kaɗan ne waɗanda suke yin imani.

89. Yayin da kuma wani littafi ya zo musu daga Allah, yana mai gaskata abin da yake tare da su, alhali kuma a da sun kasance suna addu'ar neman nasara a kan waɗanda suka kafirta (mushrikai). To yayin da abin da suka sani ya zo musu sai suka kafirce masa. Don haka la'anar Allah ta tabbata a kan kafirai.

90. Tir da wannan abu da suka sayar da kawunansu da shi, wato suka kafirce wa abin da Allah Ya saukar, don hassadar cewa, (don me) Allah zai saukar da falalarsa ga wanda Ya ga dama daga bayinsa, sai suka wayi gari da fushin Allah a kan wani fushin. Kuma azaba ta wulaƙanci ta tabbata ga kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa mana cewa, ya ba wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) littafin Attaura, sannan a bayansa ya ci gaba da aiko wasu manzannin zuwa ga al'ummar Banu Isra'ila, waɗanda suka ci gaba da aiki da shari'ar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), har zuwa lokacin da ya aiko Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya kuma bayyana gaskiyarsa ta hanyar ba shi mu'ujizoji daban-daban, kamar tayar da matattu, da warkar da marasa lafiya da izinin Allah, hakanan ya ƙarfafa shi da Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya riƙa taimaka masa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna mana ƙyamar irin ta'annutin da Banu Isra'ila suka riƙa yi wa annabawan da ya aika musu. Wato duk sa'adda wasu manzanni suka zo musu da hukunce-hukuncen da suka saɓa wa soye-soyen zukatansu, sai su ji cewa waɗannan manzanni suna matsa musu ne, kuma sun rena musu wayo, don haka sai girman kansu ya ingiza su, sai su ƙaryata wasu daga cikin waɗannan manzannin, wasu kuma ma su kashe su. Sai kuma sai suka riƙa faɗar wata ƙaryar cewa, wai su abin da ya hana su su yi imani shi ne, zukatansu a rufe suke rif, don haka ba sa iya fahintar wani abu da manzanninsu suke faɗa musu. Sai Allah ya ƙaryata su, ya nuna abin da suke inkari ba haka yake ba; kafircinsu ne kawai ya jawo Allah ya la'ance su, ya nisantar da su daga rahmarsa, sakamakon abin da suka zaɓa na bijire wa koyarwar manzanninsu da annabawansu. Saboda haka sai ya kasance 'yan kaɗan ne a cikinsu suka ba da gaskiya, ko kuma abin da suka yi imani da shi kaɗan ne ƙwarai.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba mu labarin wani hali na Yahudawa tun kafin aiko Annabi Muhammad (ﷺ) shi ne yayin da suke a Madina, duk sa'adda wani faɗa ya ɓarke tsakaninsu da Larabawa mutanen Madina masu yin shirka, sukan ce musu: "Akwai wani Annabi da za a aiko nan ba da jimawa ba; idan ya bayyana za mu bi shi, mu haɗa ƙarfi da shi, mu yi muku irin kisan da aka yi wa Adawa da Samudawa." Wato suna nufin kisan ƙare-dangi. Su Yahudawa a zatonsu Annabin zai bayyana ne daga cikinsu, sai kuma ya bayyana daga cikin Larabawa kuma Kuraishawa, abokan faɗansu.
Yayin da Annabi Muhammad (ﷺ) ya zo da littafin Alƙur'ani, wanda yake gaskata abin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da sauran annabawa suka zo da shi na Tauhidi, kuma Banu Isra'ila suka gane shi ne Annabin da suke faɗar zai bayyana, suka kuma fahinci gaskiyar da ya zo da ita, to maimakon su yi imani kamar yadda suka kasance suna shelantawa, sai kawai suka kafirce masa, a dalilin haka sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya la'ance su, ya nisantar da su daga rahmarsa. Wannan kuma shi ne sakamakon kowane kafiri a duniya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir da irin wannan mugun zaɓi da Yahudawa suka yi wa kawunansu, wato suka zaɓi su kafirce wa Annabin da suka san gaskiyarsa, suka zaɓar wa kawunansu shiga wutar Jahannama, ba don wani abu ba, sai don kawai tsabar hassada da ƙabilanci da suke yi wa Larabawa, wai don me Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai aiko da Annabi a cikinsu ba a cikin Banu Isra'ila ba, tare da cewa sun san shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayar da falalarsa ne ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa babu mai iya hana shi. Wannan ne ya sa Yahudawa suka cancanci wani fushi daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a kan fushin da suka cancanta a baya na laifukan da suka riƙa tabkawa. Don haka ne duk waɗanda za su bijire wa saƙon Annabi Muhammadu (ﷺ) a kowane zamani ne to suna da wata azaba mai wulaƙantarwa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karyar Yahudu wajen da'awar sun yi imani da Attaura, alhalin suna saɓa mata a fili da ayyukansu.

2. Wajibi ne ga mumini ya karɓi shari'ar Allah da ƙarfi da nishaɗi, ba da kasala ba.

3. Wajibi ne mutum ya karɓi gaskiya daga bakin duk wanda ya faɗe ta.

Suratul Baƙara (91-93)

وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ ءَامِنُواْ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُواْ نُؤْمِنُ بِمَآ أُنزِلَ عَلَيْنَا وَيَكْفُرُونَ بِمَا وَرَآءَهُۥ وَهُوَ ٱلْحَقُّ مُصَدِّقًا لِّمَا مَعَهُمْ ۗ قُلْ فَلِمَ تَقْتُلُونَ أَنۢبِيَآءَ ٱللَّهِ مِن قَبْلُ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٩١﴾ * وَلَقَدْ جَآءَكُم مُّوسَىٰ بِٱلْبَيِّنَٰتِ ثُمَّ ٱتَّخَذْتُمُ ٱلْعِجْلَ مِنۢ بَعْدِهِۦ وَأَنتُمْ ظَٰلِمُونَ ﴿٩٢﴾ وَإِذْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَكُمْ وَرَفَعْنَا فَوْقَكُمُ ٱلطُّورَ خُذُواْ مَآ ءَاتَيْنَٰكُم بِقُوَّةٍ وَٱسْمَعُواْ ۖ قَالُواْ سَمِعْنَا وَعَصَيْنَا وَأُشْرِبُواْ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلْعِجْلَ بِكُفْرِهِمْ ۚ قُلْ بِئْسَمَا يَأْمُرُكُم بِهِۦٓ إِيمَٰنُكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٩٣﴾

91. Idan aka ce da su: "Ku yi imani da abin da Allah Ya saukar", sai su ce: "Mu muna yin imani ne da abin da aka saukar mana". Kuma suna kafircewa da duk wani abu da ba shi ba, alhalin shi gaskiya ne, kuma mai gaskata abin da ke tare da su ne. To ka ce: "Me ya sa a da kuke kashe annabawan Allah idan kun kasance muminai?"

92. Haƙiƙa Musa ya zo muka da hujjoji bayyanannu, sannan kuka bauta wa ɗan maraƙi bayansa alhalin kuna azzalumai.

93. Kuma ku tuna lokacin da Muka ɗauki alƙawari da ku, Muka kuma ɗaga dutsen Ɗuri a kanku, Muka ce: "Ku riƙi abin da muka ba ku da ƙarfi, kuma ku saurara". Sai suka ce: "Mun ji kuma mun saɓa". Kuma aka sanya musu tsananin son bautar ɗan maraƙi a zukatansu saboda kafircinsu. Ka ce: "Tir da abin da imaninku yake umartar ku da shi, idan har kun kasance muminai."

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana yadda Banu Isra'ila suke iƙrarin cewa, su sun yi imani ne da Attaura kawai, kuma ta wadatar da su, ba sa buƙatar sai sun yi imani da Alƙur'ani. To shi ne a nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ƙaryata su, yana bayyana cewa, hatta ita ma Attaurar ba wani cikakken imani suka yi da ita ba. Duk da cewa shi Alƙur'ani Allah ya saukar da shi ne bayan Attaura, kuma yana gaskata abin da yake cikin Attaura na Tauhidi da rukunnan imani. Wannan magana tasu tubka da warwara ce, domin duk wanda ya ƙaryata Alƙur'ani, to ya ƙaryata sauran littattafan ma gaba ɗaya.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa Muhammad (ﷺ) da ya tambaye su, idan har da gaske suke sun yi imani da Attaura, me ya sa suke kashe annabawan Allah waɗanda su ma suna gaskata abin da yake cikinta? Kuma a cikin Attaura an haramta kashe kowane Annabi.
A ƙarshe sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna a fili cewa, ƙarya suke yi, ba su yi imani da Attaurar ba, domin tun farko da Annabi Musa ya zo musu da hujjoji bayyanannu masu tabbatar da gaskiyar annabcinsa, sai suka koma suna bautar ɗan maraƙi lokacin da ya tafi ganawa da Ubangijinsa saboda ƙetare iyaka da zalunci.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tuna wa Banu Isra'ila labarin lokacin da ya ɗauki alƙawari mai ƙarfi a wurinsu, har ya ɗaga dutsen Ɗuri a samansu, kamar ya rufto ya faɗo musu, domin a tsorata su a kan dole su yi aiki da umarnin da aka ba su na cewa lalle su riƙe Attaura gamgam da himma da nashaɗi, kuma su saurari maganar Allah, sauraro na karɓa da miƙa wuya, amma sai suka amsa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da cewa, sun ji da kunnuwansu, amma kuma sun saɓa da ayyukansu. Son bautar

ɗan maraƙi ya riga ya ratsa zukatansu, sun kwankwaɗe shi da gaske, kamar yadda mai jin ƙishirwa yake kwankwaɗar ruwa idan ya samu, har ya ratsa ko'ina a jikinsa.Bayanan da suka gabata sun tabbatar da cewa, imanin Yahudawa na jabu ne, tun da bai hana su kashe annabawan Allah ba, bai hana su bautar ɗan maraƙi ba, bai kuma hana su bijire wa umarnin Ubangijinsu ba. Don haka sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir da wannan imani nasu, ya tabbatar da cewa, imani na ƙwarai shi yake sanya mai shi ya aikata alheri ya kuma kauce wa sharri.

Abubuwan da za mu yi la'akari da su daga waɗannan ayoyi:

1. Tsawon rai idan ya kasace cikin sabon Allah ne, to ba shi da wani amfani ga mutum. Don haka ka roƙa wa wanda kake ƙauna jinkiri mai amfani, kamar yadda ya zo cikin addu'o'in da Annabi (ﷺ) ya koyar da al'ummarsa: "Ya Allah ka raya ni matuƙar rayuwa ce mafi alheri a gare ni, ka kuma karɓi raina idan mutuwar ce ta fi alheri a gare ni." [Bukhari #5671 da Muslim #2680]
2. Yahudawa sun fi kowa son rayuwa a duniya, saboda yadda suka fitar da ƙauna daga ni'imar lahira.

3. Allah ya nuna mana su Yahudawa da masu halaye irin nasu, suna sha'awar rayuwar duniya ce ko ma wace iri, kuma ba ruwansu da kyanta ko rashin kyanta, saɓanin Musulmi; shi yakan yin fatan rayuwa ce mai albarka a gare shi da al'ummarsa.

Suratul Baƙara (94-96)

قُلْ إِن كَانَتْ لَكُمُ ٱلدَّارُ ٱلْآخِرَةُ عِندَ ٱللَّهِ خَالِصَةً مِّن دُونِ ٱلنَّاسِ فَتَمَنَّوُا۟ ٱلْمَوْتَ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٩٤﴾ وَلَن يَتَمَنَّوْهُ أَبَدًۢا بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٩٥﴾ وَلَتَجِدَنَّهُمْ أَحْرَصَ ٱلنَّاسِ عَلَىٰ حَيَوٰةٍ وَمِنَ ٱلَّذِينَ أَشْرَكُوا۟ ۚ يَوَدُّ أَحَدُهُمْ لَوْ يُعَمَّرُ أَلْفَ سَنَةٍ وَمَا هُوَ بِمُزَحْزِحِهِۦ مِنَ ٱلْعَذَابِ أَن يُعَمَّرَ ۗ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِمَا يَعْمَلُونَ ﴿٩٦﴾

94. Ka ce: "Idan gidan lahira ya kasance keɓantacce a gare ku a wurin Allah ku kaɗai ban da sauran mutane, to ku yi burin mutuwa idan har ku masu gaskiya ne."

95. Ba za su taɓa burin mutuwa ba har abada, saboda abin da hannayensu suka aikata. Kuma Allah Masani ne ga azzalumai.

96. Kuma za ka same su sun fi kowa kwaɗayin tsawon rai, fiye ma da waɗanda suka yi shirka. Kowane ɗayansu yana burin ina ma za a raya shi shekara dubu, kuma raya shi (shekar dubu) ba zai nensanta shi daga shiga wuta ba. Kuma Allah Mai ganin abin da suka kasance suna aikatawa ne.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, idan Yahudawan Madina suna da'awar cewa, don su kaɗai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadi ni'imar gidan Aljanna a lahira, ban da sauran mutane, to ga wata hanya da za a bi a gane mai gaskiya, ita ce su haɗu su yi addu'ar tsinuwa, wato su roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halaka maƙaryaci daga cikinsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa, sam-sam Yahudawa ba za su taɓa karɓar wannan kira nasa ba, saboda suna sane da irin laifuffukan da suka tabka na kafirce wa Annabi da ɓoye gaskiya, kuma suna sane da cewa hanyar haɗuwa da mummunan sakamakon miyagun ayyukansu ita ce mutuwa; da zarar sun mutu, to sun faɗa cikin abin ƙi ke nan har abada. Wannan kaɗai ya isa ya hana su son mutuwa. To amma fa kada su manta da cewa, Allah yana sane da duk wani azzalimi mai keta dokarsa a bayan ƙasa, kuma komai daɗewa sai Allah ya damƙe shi ya nuna masa sakamakonsa.Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ai babu wani jinsi na mutane da yake gudun mutuwa irin jinsin Bayahude, domin ya

san abin da yake jiran sa a lahira na azaba, don haka za ka ga kowane ɗayansu yana son ya yi tsawon rai a duniya, ta yadda soyayyarsu da rayuwa a nan duniya, har ta zarce ta mushrikai waɗanda ma ba su yi imani da akwai ranar lahira ba, ballantana har su yarda da cewa akwai wani sakamako da zai biyo baya. Ai shi Bayahude burinsa shi ne ya rayu shekara dubu a duniya, to amma ya manata cewa, ko da an ba shi tsawon rai irin wannan, ba zai hana shi mutuwa ba, kuma da zarar ya mutu wuta ce makomarsa. Allah kuma yana ganin duk abin da suke aikatawa na miyagun ayyuka, ba abin da yake ɓuya a gare shi kuma zai yi musu sakayya a kansu ɗaya bayan ɗaya.

Suratul Baƙara (97-101)

قُلْ مَن كَانَ عَدُوًّا لِّجِبْرِيلَ فَإِنَّهُۥ نَزَّلَهُۥ عَلَىٰ قَلْبِكَ بِإِذْنِ ٱللَّهِ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ وَهُدًى وَبُشْرَىٰ لِلْمُؤْمِنِينَ ﴿٩٧﴾ مَن كَانَ عَدُوًّا لِّلَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَجِبْرِيلَ وَمِيكَىٰلَ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَدُوٌّ لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿٩٨﴾ وَلَقَدْ أَنزَلْنَآ إِلَيْكَ ءَايَٰتٍۭ بَيِّنَٰتٍ ۖ وَمَا يَكْفُرُ بِهَآ إِلَّا ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿٩٩﴾ أَوَكُلَّمَا عَٰهَدُوا۟ عَهْدًا نَّبَذَهُۥ فَرِيقٌ مِّنْهُم ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٠٠﴾ وَلَمَّا جَآءَهُمْ رَسُولٌ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ مُصَدِّقٌ لِّمَا مَعَهُمْ نَبَذَ فَرِيقٌ مِّنَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَٰبَ كِتَٰبَ ٱللَّهِ وَرَآءَ ظُهُورِهِمْ كَأَنَّهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٠١﴾

97. Ka ce: “Duk wanda ya kasance maƙiyi ne ga (Mala'ika) Jibrilu, to lalle shi ne ya saukar da shi (Alƙur'ani) a kan zuciyarka da izinin Allah yana mai gaskata abin da ya gabace shi (na littattafai), kuma shiriya ne da bushara ga muminai.”

98. Duk wanda ya kasance maƙiyi ne ga Allah da mala'ikunsa da manzanninsa da Jibrilu da Mika'ilu, to lalle Allah maƙiyin kafirai ne.

99. Kuma haƙiƙa Mun saukar maka da ayoyi bayyanannu, babu kuma mai kafirce musu sai fasiƙai.

100. Yanzu ashe duk sa'adda suka ƙulla wani alƙawari sai wani ɓangare daga cikinsu ya yi watsi da shi?! Bari! Yawancinsu ba sa yin imani.

101. Yayin da wani manzo daga Allah ya zo musu yana mai gaskata abin da yake tare da su (na Littafin Attaura), sai wani ɓangare daga cikinsu suka jefar da littafin Allah a bayansu kamar ba su san komai ba.

Imamut Tirmizi [#3117] da Imamu Ahmad [#2483] sun ruwaito hadisi daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Yahudawa sun zo wurin Manzon Allah (ﷺ) suka ce masa: “Ya Baban Alƙasim, mun zo ne mu yi maka tambaya a kan abubuwa guda biyar, idan ka ba mu amsarsu, to mun fahinci kai Annabi ne, kuma za mu bi ka. Sai Annabi (ﷺ) ya kafa musu shaida da Allah, kamar yadda Annabi Yakubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi da ‘ya’yansa, lokacin da suka ce: “Allah ne wakili bisa duk abin da za mu faɗa.” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “To ku yi tambayoyinku.” Sai suka ce: “Ka faɗa mana mece ce alamar annabi?” Sai ya ce: “Alamarsa ita ce, idanuwansa za su yi barci, amma zuciyarsa ba za ta yi ba.” Sai suka ce: “To ka faɗa mana mene ne ya sa mace wani lokaci ta haifi ‘ya mace, wani lokaci kuma ta haifi ɗa namiji?” Sai ya ce, “Idan ruwan ‘ya mace ya rinjayi ruwan ɗa namiji, to sai ta haifi ‘ya mace, idan kuwa na mijin ne ya rinjayi na matar, sai ta haifi ɗa namiji.” Sai suka ce: “To faɗa mana, wane irin abinci ne Isra’ilu (Ya’aƙub) ya haramta wa kansa?” Sai ya ce: “Ya yi fama da cutar ciwon kwankwaso da ƙafafu (*Sciatica*), bai samu wani magani da ya yi masa amfani ba, sai nonon abu kaza da abu kaza. (Imamu Ahmad ya ce wasu sun ce nonon raƙumi ne ya samu). Daga lokacin sai ya haramta wa kansa cin namansu.” Sai suka ce: “Ka yi gaskiya.”

Sannan kuma suka ce: “To faɗa mana mene ne wannan tsawar da muke ji?” Sai ya ce:“Wannan mala’ika ne da Allah ya wakilta shi don ya kula da girgije, yana ɗauke da wani takobi na wuta a hannunsa, yana kora wannan girgije da shi har zuwa inda Allah ya umarce shi.” Sai suka ce: “To, shi kuma wannan ƙarar da ake ji ta mece ce?” Sai ya ce: “Muryarsa (Mala’ikan) ce.” Sai suka ce, “Ka yi gaskiya.”
Sannan kuma suka ce masa: “To yanzu saura tambaya ɗaya ta rage, idan ka amsa mana ita, to za mu yi maka mubaya’a, domin babu wani annabi face yana da wani mala’ika da yake kawo masa labari. To ka faɗa mana kai wane ne mala’ikanka?” Sai ya ce: “Jibrilu ne (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).” Cikin mamaki, sai suka ce: “Jibrilu? Ai wannan shi ne wanda yake saukowa da yaƙi da kashe-kashe da azaba, ai wannan maƙiyinmu ne! Da dai ka ce mana mala’ika ne wanda yake saukar da rahama da tsaro da ruwan sama, da abin ya yi kyau.” Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyi (watau aya ta 97-99).” [Hadisi ne mai kyau, ban da maganar tsawa da walƙiya].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce wa Annabinsa (ﷺ) ya faɗa wa waɗannan Yahudawa cewa, duk wanda yake gaba da Mala’ika Jibrilu, to ya sani cewa, shi Jibrilu yana saukar wa da Annabi Alƙur'ani ne da umarnin Allah, ba a gaban kansa yake yi ba, don haka ba shi suke nuna wa ƙiyayya ba, Allah ne da ya aiko shi suke nuna wa ƙiyayya. Sannan kuma Alƙur'ani da yake saukar masa, koyarwar cikinsa tana daidai da abin da ya zo a littattafan annabawan da suka gabace shi, kamar Attaura. Wannan kuwa babban dalili ne da yake nuna gaskiyarsa, sannan shi Alƙur’ani babbar bushara ce ga muminai ta irin abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadar musu na ni’ima mai ɗorewa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa musu cewa, duk wanda yake ƙin Allah ko yake ƙin wani mala’ika, ko Mala’ika Jibrilu, ko Mala’ika Mika’ilu, ko yake gaba da wani manzo daga cikin manzannin Allah, to wannan kafiri ne, kuma Allah zai ɗauke shi a matsayin abokin gabarsa, domin Allah ba ya son kowane irin kafiri. Shi ya sa ya zo a hadisi ƙudusi inda Allah yake cewa: “Duk wanda ya yi gaba da wani masoyina, to lalle ina yi masa shelar yaƙi.” [Bukhari #6502].
Abdurrahman ɗan Abu Laila ya ruwaito cewa, wani Bayahude ya gamu da Sayyidina Umar (Allah ya kara masa yarda) sai ya ce masa: “Jibrilun nan da Annabinku yake ta faɗa fa maƙiyinmu ne.” Sai Umar (Allah ya kara masa yarda) ya mayar masa da martani da cewa: “Wanda duk ya kasance maƙiyin Allah da mala’ikunsa da manzanninsa….(har zuwa ƙarshen ayar).” Ya ce: “Sai wannan ayar ta sauka.” [Duba Tafsirin Ibnu Abi Hatim Juzu’i na 1, shafi na182; da *Fathul Bari* na Ibnu Hajar Juzu’i na 8, shafi na16].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, ya saukar masa da ayoyi bayyanannu, masu nuna gaskiyar annabcinsa, babu wanda yake ja da su sai wanda ba mumini ba. Allah kuma ya faɗa masa cewa, Yahudawa wasu mutane ne marasa alƙawari; duk sa’adda suka ɗaukar wa Allah alƙawarin za su yi aiki da Attaura da abin da ta ƙunsa na shari’a, to sai an samu wasu daga cikinsu sun warware alƙawarin nan sun yi jifa da shi, ba komai ya jawo haka ba, sai domin yawancinsu ba masu imani ba ne, domin da suna da imani na gaskiya, to da sun kiyaye alƙawari, ba su karya shi ba.
Daga cikin ire-iren karya alƙawarin da suka yi shi ne, ƙokacin da Allah ya aiko Annabinsa (ﷺ) ya zo kuma kamar yadda Allah ya siffanta musu shi a cikin littattafansu, kuma ya yi alƙawari da su a kan za su bi shi idan ya bayyana, to sai ga shi yanzu yawancinsu sun yi watsi da wannan alƙawarin, sun yi jifa da littafin Attaura can bayansu, kamar ba su taɓa sanin wani abu ba dangane da wannan Annabi da siffofinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya jarraba bayinsa ta hanyar hore musu wasu hanyoyi na saba masa, don ya tantance mai biyayya na gaskiya daga cikinsu, da wanda zai bijire; shi ne dalilin saukar da waɗannan mala’iku guda biyu, Harutu da Marutu a ƙasar Iraƙi.

2. Dangane da waɗannan mala’iku biyu, an samu ruwayoyi masu yawa, waɗanda aka jingina wasu daga cikinsu zuwa ga Annabi (ﷺ), wasu kuma aka dangana su ga wasu tabi’ai, kamar Mujahid da Suddi da Al-

Hasanul Basri da Katada da sauransu. To amma fa babu wani labari da ya inganta cikin irin abin da aka ruwaito; hasali ma da yawa daga ciki an samo su ne daga Banu Isra'ila.

3. Wajibi ne mutum ya yi wa ɗan'uwansa nasiha da gargaɗi, ko da kuwa ba zai karɓa ba.

4. Sababi shi kaɗai a karan kansa ba shi da wani tasiri sai da izinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka ya wajaba ga mumini ya riƙa komawa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ko da yaushe domin neman taimakonsa.

5. Duk mutumin da ya saki koyarwar Allah da Manzonsa, to ba zai zauna hakanan ba sai ka ga ya riƙe wata koyarwar da za ta cutar da shi, kuma ba za ta amfane shi da komai ba. Kamar yadda Hausawa suke cewa, wanda ya ƙi sharar masallaci, to ya yi ta kasuwa.

6. Yana daga cikin manya-manyan ɓarnace-ɓarnace da shaiɗanu suke ƙoƙarin bazawa a cikin al'umma, shi ne mace-macen aure. Shi ya sa Annabi (ﷺ) ya faɗa mana cewa: "Shaiɗan yakan ɗora kujerarsa a kan ruwa ya zauna, ya aika mayaƙansa. To duk wanda ya fi fitina daga cikin sojojinsa, shi ya fi matsayi a wurinsa. Ɗaya daga cikinsu zai zo ga Iblis ya ba shi labarin irin ɓarnar da ya yi a ranar, sai Iblis ya ce, ai bai yi komai ba. Sai kuma wani ya dawo ya ce, bai rabu da wani magidanci ba, har sai da ya ga ya raba shi da matarsa. Sai Iblis ya janyo shi kusa da shi ya ce: "Madalla da irinka." [Muslim #2813].

7. Duk mutumin da yake aiki da iliminsa, shi ne wanda yake guje wa abin da zai cutar da shi. Yayin da Yahudawa suka bar aiki da iliminsu, sai suka faɗa cikin abin da ya cutar da su duniya da lahira.

Suratul Baƙara (102-103)

وَٱتَّبَعُواْ مَا تَتۡلُواْ ٱلشَّيَٰطِينُ عَلَىٰ مُلۡكِ سُلَيۡمَٰنَۖ وَمَا كَفَرَ سُلَيۡمَٰنُ وَلَٰكِنَّ ٱلشَّيَٰطِينَ كَفَرُواْ يُعَلِّمُونَ ٱلنَّاسَ ٱلسِّحۡرَ وَمَآ أُنزِلَ عَلَى ٱلۡمَلَكَيۡنِ بِبَابِلَ هَٰرُوتَ وَمَٰرُوتَۚ وَمَا يُعَلِّمَانِ مِنۡ أَحَدٍ حَتَّىٰ يَقُولَآ إِنَّمَا نَحۡنُ فِتۡنَةٞ فَلَا تَكۡفُرۡۖ فَيَتَعَلَّمُونَ مِنۡهُمَا مَا يُفَرِّقُونَ بِهِۦ بَيۡنَ ٱلۡمَرۡءِ وَزَوۡجِهِۦۚ وَمَا هُم بِضَآرِّينَ بِهِۦ مِنۡ أَحَدٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ وَيَتَعَلَّمُونَ مَا يَضُرُّهُمۡ وَلَا يَنفَعُهُمۡۚ وَلَقَدۡ عَلِمُواْ لَمَنِ ٱشۡتَرَىٰهُ مَا لَهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنۡ خَلَٰقٖۚ وَلَبِئۡسَ مَا شَرَوۡاْ بِهِۦٓ أَنفُسَهُمۡۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ١٠٢ وَلَوۡ أَنَّهُمۡ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَوۡاْ لَمَثُوبَةٞ مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِ خَيۡرٞۚ لَّوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ١٠٣

102. Sai suka bi abin da sheɗanu suke karantawa a (zamanin) mulkin Sulaimanu; kuma Sulaimanu bai kafirta ba, sai dai sheɗanun su ne suka kafirta suna koya wa mutane tsafi da abin da aka saukar wa mala'iku biyu, Haruta da Maruta, a garin Babila. Kuma ba sa koya wa wani (tsafin) har sai sun faɗa masa cewa: "Mu fa jarraba ce, don haka kada ka kafirta". Sai (mutane) suka riƙa koyo daga wajensu su biyu abin da suke raba tsakanin miji da matarsa da shi. Kuma ba za su iya cutar da wani da shi ba sai da izinin Allah. Sai su koyi abin da zai cutar da su kuma ba zai amfane su ba. Kuma haƙiƙa sun san cewa, tabbas duk wanda ya zaɓi (sihiri) ba shi da wani rabo a lahira. Kuma tir da abin da suka sayar da kawunansu da shi, da a ce sun san (haƙiƙanin makomarsu).

103. Da a ce su sun yi imani kuma sun yi taƙawa, haƙiƙa da sakamakon (da za su samu) daga Allah shi ne mafi alheri, da a ce sun sani.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin halin da Yahudawa suka tsinci kansu a ciki, bayan sun yi watsi da littafin Allah da koyarwar annabawansu, sai suka rungumi koyarwar shaiɗanu a madadin haka, wanda sakamakon haka shi ne duk wanda ya bar koyarwar annabawa da ilimi mai amfani, to lalle a madadinsa sai ya rungumi wani ilimi marar kyau mai cutarwa. Don haka sai Yahudawa

suka rungumi ilimin sihiri, kuma suka riƙa faɗar ƙaryar cewa, shi ne ilimin da Annabi Sulaiman yake amfani da shi wajen sarrafa mulkinsa, da shi ne ya mulki mutane da aljannu, har ma da dabbobi. Sai Allah ya ƙaryata su, ya wanke Annabi Sulaiman (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga aikata duk wani tsafi, shi kuma ba kafiri ne ba, aikata tsafi kuma kafirci ne. Don haka shaiɗanu ne suka kafirta ta hanyar fitowa suna koya wa mutane sihiri domin su ɓatar da su daga kan hanya. Hakanan Yahudawa suka rungumi sihirin da aka saukar wa wasu mala'iku su biyu, wato Harutu da Marutu a garin Babila da ke ƙasar Iraƙi, domin su zama jarraba ga mutane.
Su kuma waɗannan mala'iku biyu ba sa yarda su koya wa wani sihirin, har sai sun yi masa nasiha da cewa: "Mu fa wata jarrabawa ce daga Allah, don haka kada ka yarda ka kafirta ta hanyar koyon wannan sihirin da aiki da shi." To amma duk da wannan nasihar tasu, sai mutane suka riƙa koyon sihiri daga wajensu, suna aikata miyagun ayyuka da su, kamar na raba tsakanin ma'aurata biyu masu ƙaunar juna. Kuma su waɗannan matsafa ba su da ikon su cutar da wani da tsafinsu sai da izinin Allah da ganin damarsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Yahudawan nan da suka yi watsi da littafin Allah, suka kafirce wa Annabi (ﷺ) suka riƙi tsafi da matsafa bayan sun san cewa, sun yi wa kansu zaɓin tumun-dare ne, sun saki reshe ne sun kama ganye, domin kuwa ba su da wani rabo a lahira daga gidan Aljanna. To Allah ya yi tir da irin wannan zaɓi na banza da suka yi wa kansu; da kuma sun san yadda suka sayar da kawunansu da rabonsu na lahira a kan wani abu ƙanƙani wanda zai cutar da su duniya da lahira to da ba su aikata haka ba. Kuma da sun nutsu sun tsaya sun zaɓi imani da tsoron Allah maimakon tsafi, to da Allah ya saka musu da mafificin abin da suke nema a nan duniya na irin amfanin da suke hangowa a cikin koyon sihiri da aiki da shi.

Suratul Baƙara (104)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقُولُواْ رَٰعِنَا وَقُولُواْ ٱنظُرْنَا وَٱسْمَعُواْۗ وَلِلْكَٰفِرِينَ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١٠٤﴾

104. Ya ku waɗanda suka yi imani kada ku ce, *ra'ina*, (watau kula da mu), sai dai ku ce, dakata mana, kuma ku saurara. Kafirai kuma suna da wata azaba mai raɗaɗi.

Sahabban Annabi (ﷺ) sun kasance idan yana biya musu karatu sukan nemi ya ɗan dakata musu kaɗan domin su fahinci karatun sosai, to sai sukan yi amfani da kalmar *'ra'ina'*. A harshen Yahudawa kuma wannan kalmar tana kusa da wata kalma da take da ma'anar 'daƙiƙi', to sai su ma suka riƙa fakewa da wannan kalmar, suna zagin Annabi (ﷺ). Sai Allah ya saukar da wannan ayar, yana hana sahabbai amfani da wannan kalmar, a maimakonta ya ce su yi amfani da kalmar '*unzurna*' wadda take nufin 'dakata mana'. Kuma Allah ya umarce su da su saurari abin da Annabi (ﷺ) yake karantar da su sauraro na fahinta, kuma ya ba da labarin cewa kafirai masu gardama da ayoyin Allah, kamar Yahudawa da sauransu, suna da wata azaba mai raɗaɗi a lahira.
Wannan ayar tana karantar da mu cewa, duk sa'adda muke amfani da wata kalma, ko wata magana, ya zamana maƙiya Musulunci suna yi mata muguwar fassara domin tana ɗauke da ma'ana mai harshen damo, to ya wajaba mu kauce mata, mu canza ta da wata kalmar da ba za a samu irin wannan matsalar tare da ita ba.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wannan ayar tana nuna irin yadda ma'abota littafi suke ɗauke da matsananciyar hassada ga Musulmi da ƙoƙarin ganin ba su bar wani abu na alherin duniya da lahira ya kai gare su ba, saboda haka ya zama wajibi a kan duk wani Musulmi ya san da haka yayin da yake mu'amala ta halal da su. Kada ya yarda ya saki jiki da su gaba ɗaya, ballantana har ya riƙa faɗa musu asirin 'yan'uwansa Musulmi.

2. A wannan ayar kuma akwai ishara cewa, son da wani yake yi ma wani, ba shi ne zai samar masa wani alheri daga Allah ba, hakanan ƙiyayyar maƙiyi ba ta iya hana wani alheri da Allah ya nufa ga bawansa.

Suratul Baƙara (105)

مَّا يَوَدُّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ وَلَا ٱلۡمُشۡرِكِينَ أَن يُنَزَّلَ عَلَيۡكُم مِّنۡ خَيۡرٖ مِّن رَّبِّكُمۡۚ وَٱللَّهُ يَخۡتَصُّ بِرَحۡمَتِهِۦ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ١٠٥

105. Waɗanda suka kafirta daga ma'abota littafi da mushrikai ba sa ƙaunar a saukar muku da wani alheri daga Ubangjinku, sai dai Allah kuwa Yana keɓance wanda Ya ga dama da rahamarsa, Allah kuma Mai babbar falala ne.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗin halayen Yahudawa da Nasara har ma da mushrikai, na irin baƙin cikin da suke yi wa Annabi (ﷺ) da muminai, wai me zai sa Allah ya waro wani daga cikinsu ya ba shi annabta? To sai Allah ya mayar musu da martani cewa, yana keɓance wanda ya ga dama da rahmarsa ne, kamar ta annabci da manzanci da ilimi, don haka ne ya zaɓi Annabi (ﷺ) da annabci da manzanci, ya kuma saukar masa da Alƙur'ani. Shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) falalarsa da rahmarsa masu yalwa ne masu girma.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwan kamar haka:

1. Hukunce-hukuncen Allah sukan zo daban-daban wajen maslaharsu ga bayinsa, a lokuta daban-daban, don haka akwai hukuncin da Allah ya saukar wa muminai a wani lokaci don maslaharsu ta wannan lokacin, daga baya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya canza shi da wani domin ganin maslahar wancan na farko ta zo ƙarshe.

2. Yana daga cikin shafe hukunce-hukunce na shari'a, a aiko annabawa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da suke ɗauke da shari'o'in da suka saɓa wa na annabawan da suka gabace su, kamar yadda Annabi Isa yake bayyanawa, yadda ya zo a *Suratu Ali-Imran*, aya ta 50.

3. Wanda duk ya yarda da cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai iko ne a kan ya zo da abubuwa a halittar sama da ƙasa daban-daban, ya canza su yadda ya ga dama, to dole ne ya yarda da cewa, yana da ikon da zai canza hukunce-hukuncensa yadda ya ga dama.

Suratul Baƙara (106-107)

۞ مَا نَنسَخۡ مِنۡ ءَايَةٍ أَوۡ نُنسِهَا نَأۡتِ بِخَيۡرٖ مِّنۡهَآ أَوۡ مِثۡلِهَآۗ أَلَمۡ تَعۡلَمۡ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ١٠٦ أَلَمۡ تَعۡلَمۡ أَنَّ ٱللَّهَ لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٍ ١٠٧

106. Babu wata aya da za Mu shafe ko Mu mantar da kai ita, sai Mun kawo wadda ta fi ta alheri ko kwatankwacinta. Ashe ba ka san cewa, lalle Allah Mai iko ne a kan komai ba?

107. Kuma ba ka sani ba cewa, lalle mulkin sammai da ƙasa na Allah ne, kuma ba ku da wani majiɓinci ko wani mai taimako ba Allah ba?

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da mayar da martani a kan wata ƙarya da Yahudawa suka fito da ita domin sukan Alƙur'ani, ita ce ƙaryata cewa Allah idan ya ga dama yana canza wani hukunci na shari’a da ya saukar da wani daban wanda yake tattare da maslaha kamar na farkon, ko ma ya zamana mafi alheri. To shi ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake faɗa cewa, babu wani hukunci na wata aya da zai shafe, ya kawo wani sabo a madadinsa, ko kuma wata aya da Allah zai goge ta daga zuciyar Annabi (ﷺ) da sahabbansa (Allah ya kara masa yarda), ko kuma ya jinkirta saukar da ita, face sai ya saukar da wata ayar da ta fi wadda ya shafe, ta fuskar amfani da maslaha ga ɗan'adam. Allah yana yin haka ne domin ya nuna cikar ikonsa a kan komai, domin kuwa matuƙar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mamallakin komai da ke sama da abin da yake ƙasa, kuma shi ne mai iko da su, yana sarrafa hukuncinsa a kan bayinsa yadda ya ga dama, to wajibi ne mu yarda da cikakken ikonsa a kan hukunci ga bayinsa yadda ya ga dama, ya halatta abin da ya ga dama, ko ya haramta, domin babu mai masa gyara a kan aikinsa, mu kuma bayinsa ne, ban da shi ba mu da wani wanda zai iya taimaka mana ya kare mu daga duk wani sharri.

Suratul Baƙara (108)

أَمْ تُرِيدُونَ أَن تَسْـَٔلُوا۟ رَسُولَكُمْ كَمَا سُئِلَ مُوسَىٰ مِن قَبْلُ ۗ وَمَن يَتَبَدَّلِ ٱلْكُفْرَ بِٱلْإِيمَٰنِ فَقَدْ ضَلَّ سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ﴿١٠٨﴾

108. Ko kuma kuna nufin za ku tambayi Manzonku kamar yadda aka yi wa Musa tambaya a da? Kuma duk wanda ya canza imani da kafirci to haƙiƙa ya ɓace wa tsakiyar hanya.

Daga nan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da yi mana bayani game da irin tambayoyin ƙure da wasu suka riƙa yi wa Manzon Allah (ﷺ), suna cewa idan har ya iya biya musu waɗannan buƙatu nasu, to a lokacin ne za su yi imani da shi. Kamar yadda Abdullah ɗan Abbas ya ce, Rafi’u ɗan Huraimilah da Wahabu ɗan Zaidu sun ce wa Manzon Allah (ﷺ): “Ka hau sama ka zo mana da wani littafi a rubuce da za mu karanta, ko ka ɓulɓulo mana da ƙoramu, idan ka yi hakan, to za mu yarda da kai mu bi ka.” Sai Allah ya saukar da waɗannan ayoyi, yana jan kunnen muminai da kafirai da su guji irin waɗannan tambayoyi da buƙatu na ƙoƙarin ƙure Manzon Allah (ﷺ), ko nuna masa rashin gamsuwa da abin da ya zo da shi na shiriya, kamar yadda Yahudawan farko suka riƙa yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) irin waɗannan tamboyi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin tambayoyin ƙwaƙwa da Yahudawa suka yi ta yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a wannan Sura, aya ta 55 da 61 da 68-71 da Suratun *Nisa’i*, aya ta 133.
Hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin waɗannan buƙatu da Kuraishawa suka riƙa bijiro wa Annabi (ﷺ) da su, domin su nuna gazawarsa, daga bisani su sami hujja a kan ƙaryata shi da suke yi, kamar yadda ya zo a cikin *Suratul Isra’i* aya ta 89-93. To saboda irin waɗannan tambayoyi wasu daga cikinsu kafirci ne ƙarara, wasu kuma za su iya kaiwa ga kafirci, sai Allah ya yi gargaɗi a kan hakan da cewa, duk wanda ya musanya imaninsa da kafirci, to lalle wannan ya kauce wa hanyar Allah, ya kama hanyar halaka da taɓewa.
Ayar ta nuna rashin halaccin tambayoyi marasa ma’ana a addini, ko na nuna rashin amincewa da wani umarni na Allah da Manzonsa, domin yin haka yana nuna rashin sallamawa ta gaba ɗaya ga Allah da Manzonsa (ﷺ). Hadisai na Annabi (ﷺ) sun zo da yawa masu nuna haramcin tambayar ƙwaƙwa, daga cikinsu akwai hadisin Sa’ad Ibn Abi Waƙƙas, ya ce, Annabi (ﷺ) ya ce: “Musulmin da ya fi kowa laifi shi ne wanda ya yi tambaya a kan abin da ba a haramta ba, sai aka haramta shi saboda wannan tambayar tasa.” [Bukhari #7289, Muslim #2358]. Da kuma hadisin da Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya rawaito ya ce, Annabi (ﷺ) ya yi mana huɗuba a cikinta yake cewa: “Ya ku mutane, Allah ya wajabta muku aikin Hajji, don haka ku je Hajji.” Sai wani mutum ya yi tambaya: “A duk shekara ya Manzon Allah?” Annabi (ﷺ) ya yi shiru bai amsa masa ba, ya sake maimaitawa, Annabi bai amsa masa ba, har

sau uku. Daga nan sai Annabi (ﷺ) ya ce, “Da na ce na’am, to da ya wajaba, kuma da ba za ku iya ba.” Sannan ya ce: “Ku ƙyale ni matuƙar na ƙyale ku, domin abin da ya ja waɗanda suka gabace ku suka halaka shi ne yawan tambayoyinsu da saɓa wa annabawansu. Don haka idan na umarce ku da wani abu, to ku aikata abin da za ku iya, idan kuwa na hana ku wani abu, to ku bar shi.” [Muslim #1373].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin hassadar maƙiyan Musulunci ga Musulmai, ta yadda suke burin ina ma duk su yi ridda su koma kafirci.

2. Hassadar yawancin Yahudawa da Nasara ga Musulmi ba hassada ce ta rashin fahintar gaskiya ba, a’a, sun fahinci gaskiyar Annabi (ﷺ), domin sun ga hujjoji da dama a kan hakan, to amma hassada ta riga ta mamaye zukatansu, ba za su iya dainawa ba.

3. Mutumin da yake ƙin abu saboda ya jahilce shi, yana da ɗan wani hanzari da uzuri da za a yi masa fiye da mutumin da yake hassada ga abin da ya san gaskiya ne.

4. Tsayar da salla yadda ya kamata da fitar da zakka, suna daga cikin dalilan samun nasara daga Allah.
5. Musulunci yana umarni da yin afuwa da yafiya ga wanda ya munana, har zuwa lokacin da Allah zai nufe shi da fahinta, ko kuma ya yi maganin sa.

6. Yin afuwa da yafiya ba shi yake nuna Musulmi su zura ido su riƙa ba da kai bori yana hawa ba, a’a, dole ne su ma su ci gaba da gwagwarmayar tabbatar da haƙƙoƙinsu ta duk wata halattaciyar hanya da Allah ya yarda da ita.

Suratul Baƙara (109-110)

وَدَّ كَثِيرٌ مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ لَوْ يَرُدُّونَكُم مِّنۢ بَعْدِ إِيمَٰنِكُمْ كُفَّارًا حَسَدًا مِّنْ عِندِ أَنفُسِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلْحَقُّ ۖ فَٱعْفُوا۟ وَٱصْفَحُوا۟ حَتَّىٰ يَأْتِىَ ٱللَّهُ بِأَمْرِهِۦٓ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٠٩﴾ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ۚ وَمَا تُقَدِّمُوا۟ لِأَنفُسِكُم مِّنْ خَيْرٍ تَجِدُوهُ عِندَ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿١١٠﴾

109. Da yawa daga cikin ma'abota littafi sun yi burin ina ma a ce su mayar da ku kafirai bayan imaninku, saboda hassada daga zukatansu, bayan kuma gaskiya ta bayyana a gare su. Don haka ku yi afuwa ku kawar da kai har sai Allah Ya zo da al'amarinsa. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai.

110. Kuma ku tsayar da salla ku kuma ba da zakka; kuma duk abin da kuka aikata na alheri domin kawunanku za ku same shi a wajen Allah. Lalle Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba ne da bayyana miyagun ɗabi’u na Yahudawa da Nasara da irin hassadar da zukatansu suke ɗauke da ita dangane da shi Annabi (ﷺ) da kuma Musulmai, saboda ganin falalar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu ta aiko musu da Annabi daga cikinsu da saukar masa Alƙur'ani mai cike da hikima da tsari. Wannan ya sa Yahudawa da Nasara suka riƙa fatan ina ma muminai za su yi ridda, su bar wannan addinin na Musulunci, duk a taru a zama ɗaya wajen kafirce wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Manzonsa (ﷺ) da littafinsa Alƙur'ani. To sai Allah ya umarci muminai da su yi afuwa game da irin miyagun maganganun da suke fitowa daga bakunan maƙiyansu, su kawar da kai, domin suna yin haka ne da nufin su tunzura su har su kai ga ɗaukar wani mataki cikin fushi da ɓacin rai, wanda kuma yin hakan zai iya jawo rashin fahintar Musuluncin. Saboda haka Allah (Mai tsarki da

ɗaukaka) ya neme su da su kai zuciyarsu nesa, su yi watsi da duk wanda ya faɗa musu wata baƙar magana, su ƙyale shi har zuwa lokacin da umarnin Allah ko wani al'amarin zai zo, wato lokacin da za su nemi auka musu da yaƙi, su kuma Musulmi a umarce su da su tashi su kare addininsu da rayukansu, a nan ne Allah zai nuna musu fushinsa da azabarsa, kamar yadda ya faru ga Yahudawan Banun Nadhir da na Banu Kuraiza da Banu Kainuƙa'a, na kisa da korar da Annabi (ﷺ) ya yi musu daga Madina.
Don haka muminai su ci gaba da addininsu kamar yadda Allah ya umarce su, su tsayar da salloli a lokutansu da kula da fitar da zakkar dukiyoyinsu domin taimaka wa mabuƙata, kuma kada su manta da alƙawarin da Allah ya yi musu na cewa, duk abin da suka yi na alheri, to ladansa yana nan a wurin Allah, ba zai tozarta ba, saboda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ganin duk abin da suke aikatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsayawar mutum yana ta kuri da cika baki, ba tare da ya yi wani aiki na ƙwarai ba a nan duniya, wannan ba zai taɓa amfanarsa a lahira ba.

2. Saboda cikakken adalci na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) dubi yadda ya neme su da su kawo hujja, duk kuwa da ya riga ya san su maƙaryata ne, ba su da wata hujja, to amma saboda yankan hanzari sai ya ce da Ma'aiki (ﷺ) da ya neme su da su kawo hujjarsu, idan sun kasance masu gaskiya.

3. Aya ta (112) tana nuna Allah ba ya karɓar wani aiki na ibada sai ya cika sharuɗɗa guda biyu:
Na farko: Yi don Allah shi kaɗai, ba tare da haɗa shi da kowa ba, wannan shi ake kira ikhlasi.
Na biyu: Yin aikin daidai da koyarwa ta Annabi (ﷺ), ba tare da ƙari ko ragi ba, wato bidi'a kenan.

Suratul Baƙara (111-112)

وَقَالُواْ لَن يَدۡخُلَ ٱلۡجَنَّةَ إِلَّا مَن كَانَ هُودًا أَوۡ نَصَٰرَىٰۗ تِلۡكَ أَمَانِيُّهُمۡۗ قُلۡ هَاتُواْ بُرۡهَٰنَكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ١١١ بَلَىٰۚ مَنۡ أَسۡلَمَ وَجۡهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ فَلَهُۥٓ أَجۡرُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦ وَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ١١٢

111. Kuma (Yahudawa da Nasara) suka ce: "Babu mai shiga Aljanna sai wanda ya kasance Bayahude ko Banasare". Waɗannan burace-buracensu ne. Ka ce: "Ku kawo hujjarku idan kun kasance masu gaskiya".

112. E! Wanda ya miƙa fuskarsa ga Allah alhali yana mai kyautata aikinsa, to yana da ladansa a wajen Ubangijinsa, kuma babu tsoro a tare da su kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi mana bayanin irin ƙarairayi da cika baki na Yahudawa da Nasara da maganganu marasa kai, da babu hujja da dalili. Yahudawa sun riƙa cika baki suna cewa, wai in ban da Yahudu babu mai shiga Aljanna a ranar lahira; su ma Nasara ta ɓangarensu suka riƙa holoƙon cewa, su kaɗai ne 'yan Aljanna. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa su su duka ya mayar musu da martani iri ɗaya da cewa, duk waɗannan maganganu nasu burace-burace ne da ƙarairayi kawai, ba su da wata hujja da za su iya nunawa, idan kuwa ba haka ne ba, to su fito da hujjarsu su nuna idan su masu gaskiya ne. Maganar gaskiya dai ita ce, Musulmai su ne kaɗai 'yan Aljanna, domin gidan Aljanna yana ga wanda ya miƙa kansa ga Allah shi kaɗai, ya yi aiki na ƙwarai ba tare da shirka ba, sannan ya bi shari'ar Annabi (ﷺ) sau-da-ƙafa. To wannan shi ne Musulmi, kuma yana da ladansa a wurin Allah a ranar lahira, wanda da ma shi ne gidan Aljanna. Don haka irin waɗannan mutane su ne waɗanda babu wani tsoro a tattare da su game da abin da za su tarar a lahira, kuma ba wani baƙin ciki tare da su dangane da abin da duk suka bari a nan duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saɓa wa Allah da ilimi ya fi muni fiye da saɓa masa bisa jahilci.

2. Gargaɗi da jan kunne game da gina hukunci na addini a kan ra'ayin riƙau, da jifan wani da kafirci da ɓata, ba tare da wani dalili ba.

3. Masu gaskiya cikin wannan al'umma sun siffatu da aiki da littafin Allah da sunnar Annabi (ﷺ) da koyi da magabata na ƙwarai, saɓanin mabiya bidi'a, waɗanda suke karkace wa wannnan koyarwa, sannan suna ganin su ne a kan shiriya, masu saɓa musu kuma a kan ɓata.

4. Imanin bawa ba zai inganta ba, sai ya yarda da duk littattafan da Allah ya saukar, idan ba haka ba, to ya tabbata a kan ɓata.

Suratul Baƙara (113)

وَقَالَتِ ٱلۡيَهُودُ لَيۡسَتِ ٱلنَّصَٰرَىٰ عَلَىٰ شَيۡءٖ وَقَالَتِ ٱلنَّصَٰرَىٰ لَيۡسَتِ ٱلۡيَهُودُ عَلَىٰ شَيۡءٖ وَهُمۡ يَتۡلُونَ ٱلۡكِتَٰبَۗ كَذَٰلِكَ قَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَ مِثۡلَ قَوۡلِهِمۡۚ فَٱللَّهُ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ١١٣

113. Yahudawa suka ce: "Nasara ba a kan komai suke ba", su ma Nasara suka ce: "Yahudawa ba a kan komai suke ba", alhalin dukkansu suna karanta Littafi. Kamar haka ne waɗanda ba su da ilimi suka yi irin maganarsu. Kuma Allah zai yi hukunci a tsakaninsu ranar Alƙiyama a kan abin da suka kasance suna saɓani a cikinsa.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana surutan wofi na suka da Yahudawa da Nasara suke yi wa junansu, kowanne ɓangare yana nuna ɗan'uwansa a matsayin ɓatacce. Yahudawa sun kafirce wa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Attaura sun kuma ƙi yarda da gaskiyar da take wurin Nasara, su ma Nasara sun kafirce wa gaskiyar da take wurin Yahudawa, alhalin dukkansu suna karanta littattafan da ke hannunsu, waɗanda a cikinsu akwai abubuwan da suke ƙaryata iƙrarinsu. Injila ta ƙunshi gaskata Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), Attaura ma tana ɗauke da busharar bayyanar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ingancin annabcinsa, amma duk sun sa ƙafa sun shure waɗannan bayanai. Allah ya nuna irin waɗannan maganganu da suke yi, maganganu ne irin na jahilai marasa ilimi. To Allah zai yi hukunci a tsakaninsu, zai bayyana musu gaskiyar mai gaskiya, da kuma ƙaryar maƙaryaci a ranar alƙiyama, ranar da babu mai kuɓuta daga azabar Allah, sai wanda ya ba da gaskiya da duka annabawan Allah.
Masana tafsirin Alkur'ani sun yi saɓani dangane da waɗanda Allah yake nufi a wannan aya, kamar haka:
1. Ayar tana magana ne a kan mushrikan Kuraishawa, waɗanda suka hana Annabi (ﷺ) da Musulmi shiga masallaci mai alfarma na Makka. Daga cikin masu wannan fahinta akwai Al-Hafiz Ibn Kasir [1:388] da Al-Allamah Ibn Ashur [1:678].
2. Wasu suka ce, ana nufin Nasara waɗanda suka taimaka wa Bukhtanassar (Nebuchadnezzar) wajen rushe masallacin Baitul Maƙadis da hana muminan Banu Isra'ila salla a cikinsa. Cikin masu wannan ra'ayi akwai Al-Imam Ibn Jarir [2:422].
3. Wasu kuma suna ganin ayar ta shafi duk wanda ya yi irin wannan aiki a da da yanzu har ma da nan gaba. Daga cikin masu wannan fahinta akwai Ibnu Aɗiyyah [1:199] da Kurɗubi [1:458].
4. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman mulkinsa da faffaɗan iliiminsa, da cewa duniya gaba ɗayanta gabas da yamma da abin da ke tsakaninsu, duk nasa ne, mulkinsa ne, don haka duk inda bawa ya fuskanta, to ya fuskanci fuskar Allah ne. Don haka yayin da mai salla ya kasa fayyace alƙiblar salla, ya yi iya ƙoƙarinsa wajen gano alƙibla, to nan ma a duk inda ya fuskanta ya yi sallarsa

alƙiblar ce a wurin Allah, ko da kuwa ya kuskure wajen gano ta. Hakanan matafiyi yayin da zai yi sallar nafila a kan abin hawansa, to duk inda yake fuskanta nan ma alƙibla ce, kamar yadda ya zo a cikin sunnar Annabi (ﷺ). [Muslim #700].

Suratul Baƙara (114-115)

وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن مَّنَعَ مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ أَن يُذْكَرَ فِيهَا ٱسْمُهُۥ وَسَعَىٰ فِى خَرَابِهَآ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ مَا كَانَ لَهُمْ أَن يَدْخُلُوهَآ إِلَّا خَآئِفِينَ ۚ لَهُمْ فِى ٱلدُّنْيَا خِزْىٌ وَلَهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿١١٤﴾ وَلِلَّهِ ٱلْمَشْرِقُ وَٱلْمَغْرِبُ ۚ فَأَيْنَمَا تُوَلُّوا۟ فَثَمَّ وَجْهُ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿١١٥﴾

114. Wane ne mafi zalunci kamar wanda ya hana masallatan Allah a riƙa ambaton sunansa a cikinsu, ya yi ta ƙoƙari wajen rushe su? Waɗannan bai kamata su shige su ba sai a cikin halin tsoro. Za su gamu da wulaƙanci a duniya a lahira kuma suna da wata azaba mai girma.

115. Gabas da yamma kuma na Allah ne. Duk inda aka fuskantar da ku to can ma alƙiblar Allah ce. Lalle Allah Mai yalwar falala ne, kuma Mai yawan sani.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wanda ya fi kowa zalunci da ta'addanci cikin masu laifi, watau shi ne wanda ya hana bayin Allah ambaton Allah da bauta masa a masallatan Allah, ya tashi tsaye wajen rusa masallatan da lalata su. To irin waɗannan azzalumai, Allah ya sanya uƙubarsu ita ce, kada a bar su su shiga masallatan sai cikin halin tsoro da fargaba, watau lokacin da Allah ya ba wa muminai iko da galaba a kansu. Ko kuma ana nufin Allah zai jefa tsoro da firgici a zuƙatansu yayin da suka zo shiga waɗannan masallatai don gudun azabar da Allah zai jefa musu, duk da haka kuma suna tare da ƙasƙanci da kunya ta nan duniya, da kuma azaba mai girma a lahira da take jiran su.

Suratul Baƙara (116-117)

وَقَالُوا۟ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدًا ۗ سُبْحَٰنَهُۥ ۖ بَل لَّهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ كُلٌّ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ﴿١١٦﴾ بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ وَإِذَا قَضَىٰٓ أَمْرًا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿١١٧﴾

116. Kuma suka ce: "Allah Yana da ɗa". Tsarki ya tabbata a gare Shi. Bari wannan magana! Duk abin da yake cikin sammai da ƙasa nasa ne, kuma dukkansu masu biyayya ne a gare Shi.

117. Shi ne Wanda Ya ƙirƙiri halittar sammai da ƙasa; kuma idan zai zartar da wani al'amari sai kawai Ya ce da shi: "Kasance", sai ya kasance.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana mayar da martani ne ga masu cewa Allah yana da ɗa! Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani ta fuskoki guda shida:
Fuska Ta Farko: Allah tsarkakakken Sarki ne, bai dace da a jingina masa ɗa ba, domin shi mawadaci ne da Zatinsa, kuma shi mai kamala ne; buƙatuwa zuwa ga ɗa kuma tana nuna gajiyawa ko tawaya, waɗannan siffofi ne da Allah ya tsarkaka daga gare su.
Fuska Ta Biyu: Allah shi ne mamallakin sammai da ƙassai, da duk abin da suka ƙunsa, shi ne ya halicce su, kuma yake gudanar da ikonsa a cikinsu; dukkansu kuma bayinsa ne, shi kuma Ubangijinsu ne. Ɗa kuwa yana samuwa ne daga wasu abubuwa guda biyu waɗanda suka dace da juna. Watau ɗabi'a ta nuna cewa, ɗa wani ɓangare ne na mahaifinsa, to ashe ba zai zamo mahaluƙi ba ke nan ko kuma bawa ga Allah idan an ce shi wani sashe ne daga gare shi, kuma irinsa ne a kamanni. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ba shi da wani mai kama da shi, kuma babu mai tarayya da shi a cikin sifofinsa da ayyukansa da mulkinsa, don haka ya tsarkaka daga a jingina masa ɗa.

Fuska Ta Uku: Gamewar mulkinsa ga ɗaukacin halitta ita ta tabbatar da wadatuwarsa ga samun ɗa.Fuska Ta Huɗu: Duk wani mahaluƙi, mai ɗa'a ne ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), mai miƙa wuya ne gare shi, har shi kansa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), mai saduda ne ya bi tsari na Mahaliccinsa a rayuwarsa, ya ƙi ko ya so, kamar yadda Allah ya bayyana a *Suratul Isra'i*, aya ta 44, da *Suratur Ra'ad* , aya ta 15.
Fuska Ta Biyar: Wanda ya ƙirƙiri halittar sammai da ƙasa, ba tare da ya kwaikwaya daga wurin wani ba, duk da irin girmansu da manyan ayoyi da ke cikinsu. To yanzu wanda zai yi irin wannan gagarumin aiki, sai kuma a ce ya kasa yin wanda bai kai shi girma ba, kamar samar da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba tare da uba ba? To don me za su fitar da Annabi Isa daga cikin tsarin Kudurarsa, su mayar da shi abokin tarayya ga Allah, ko wani ɓangare nasa, har su kira shi ɗan Allah?
Fuska Ta Shida: Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan zartar da abin da duk ya yi nufin halittarsa ne da kalmar '*kun'*, wato 'kasance', sai wannan abu ya kasance, ya samu kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake son samar da shi. To ta wannan hanyar ne ya halicci Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Saboda haka duk wanda yake gudanar da aikinsa ta irin wannan hanyar, ba ya da buƙatar haihuwa, domin haihuwa hanya ce ta mahluƙi ajizi, Allah kuwa tsarkakakke ne daga wannan.

Suratul Baƙara (118-119)

وَقَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَ لَوۡلَا يُكَلِّمُنَا ٱللَّهُ أَوۡ تَأۡتِينَآ ءَايَةٞۗ كَذَٰلِكَ قَالَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِم مِّثۡلَ قَوۡلِهِمۡۘ تَشَٰبَهَتۡ قُلُوبُهُمۡۗ قَدۡ بَيَّنَّا ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يُوقِنُونَ ١١٨ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَٰكَ بِٱلۡحَقِّ بَشِيرٗا وَنَذِيرٗاۖ وَلَا تُسۡـَٔلُ عَنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلۡجَحِيمِ ١١٩

118. Waɗanda ba su da ilimi kuma suka ce, "Me zai hana Allah Ya yi magana da mu ko kuma wata aya ta zo mana?" Kamar haka ne waɗanda suka gabace su suka faɗi irin wannan maganar tasu. Zukatansu sun yi kama da juna. Haƙiƙa mun yi bayanin ayoyi ga mutane masu sakankancewa.

119. Lalle Mu Mun aiko ka da gaskiya, kana mai albishir kuma kana mai gargaɗi, ba kuma za a tambaye ka ba game da 'yan wutar Jahima.

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, mushrikan Larabawa, waɗanda ba su da ilimi irin na ma'abota littafi, suna ganin su suka fi cancanta Allah ya yi musu magana kai-tsaye, ba ta hanyar Annabi Muhammadu (Mai tsarki da ɗaukaka) ba, don haka suna ganin babu buƙatar sai Allah ya aiko da wani Annabi na musamman, sai dai kawai ya yi magana da mutane kai-tsaye, ya faɗi umarninsa da haninsa. Wannan ba shakka jahilci ne wanda bai kamata a ce ma'abota littafi sun auka cikinsa ba, domin ko su sun yarda da aiko annabawa da manzanni.
Hakanan kuma suka riƙa neman a zo musu da wata aya, duk da cewa, Annabi (ﷺ) ya zo da mu'ujizoji masu yawa, amma duk suka nuna ba su gamsu ba, suka ƙirƙiri wasu buƙatu suka ce sai Annabi (ﷺ) ya cika musu su sannan za su yi imani da shi. Duk kuma suna yin haka ne domin nuna taurin kansu da kangarewarsu, ba wai niyyarsu su yi imani ba, kamar yadda ya zo a cikin *Suratul Isra'i*, aya ta 90-93.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) har wa yau ya bayyana cewa, irin waɗannan buƙatu nasu na neman a kawo musu ayoyi irinsa ne al'ummomin da suka gabace su, kamar Yahudu da Nasara, suka riƙa gabatar wa da annabawansu, kamar yadda ya zo a *Suratu An-Nisa'i*, aya ta 159. Allah ya nuna mana cewa zukatan mushrikan Larabawa sun yi kama da zukatan Yahudu da Nasara wajen fito-na-fito da gaskiya da taurin kai da kangare wa annabawa, shi ne ya sa ayyukansu ma suka zama iri ɗaya. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, ya fito da duk wasu ayoyi ko dalilai masu tabbatar da gaskiyar annabcin Annabi (ﷺ), ta yadda babu buƙatar sake wata tambaya a kai, sai dai wannan bayani da Allah yake yi, babu mai fa'idantuwa da shi sai mutane masu yaƙini a zukatansu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da magana da Annabinsa (ﷺ), yana jaddada masa cewa, ya aiko shi ne da gaskiya, don haka aikowarsa gaskiya ce, abin da ya zo da shi ma gaskiya ne, kuma ya

ɗora masa nauyin ya isar da saƙo na bushara ga duk wanda ya bi shi, ya isar da saƙo na gargaɗi ga duk wanda ya bijire masa cikin mutane da aljannu. Don haka babu wani laifi da za a kama shi da shi, don wasu sun ci gaba da zama cikin kafircinsu, sun ƙi yin imani da shi, bayan ya isar musu da saƙon gaskiya da aka aiko shi da shi. Waɗannan mutane ‘yan wuta ne, kuma masu dawwama ne a cikinta har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk kafirci addini ɗaya ne, shi ya sa Allah ya ce ‘addininsu’, duk kuwa da cewa addinin Yahudawa daban yake da na Nasara.

2. Rigimar da take tsakanin Musulmai da waɗanda ba Musulmai ba, ita ce rigimar aƙida, ba rigima a kan ƙasa ko tattalin arziki ko wani mulki na duniya ba. Waɗannan duk wata rumfa ce da aka fake a ƙarƙashinta domin cim ma waccan manufa guda ɗaya, watau raba Musulmi da aƙidarsa ta Musulunci.

3. Duk wani ra’ayi ko karantarwa ko ibada wadda ta saɓa wa karantarwar Allah da Manzonsa (ﷺ), to son zuciya ce. Shi ya sa aka kira ‘yan bidi’a da sunan mabiya son zuciya.

4. Abin da Yahudu da Nasara suke yi da sunan addini, to ba addini ba ne a wurin Allah, sunansa son zuciya.

5. Wanda ya bi son zuciyarsa bayan ilimi ya zo masa, to wannan ya fi taɓewa fiye da wanda ba shi da ilimi.

6. Wanda duk ya bar hanyar Allah da shiriyarsa, to ba zai taɓa samun mai kare shi daga kamun Allah ba, duk yawan jama’arsa ko sojojinsa, ko masu tsaronsa. Domin ana samun taimakon Allah ne ta hanyar bin shiriyarsa.

7. Karanta littafin Allah (ﷺ) da aiki da shi, shi ne alamar imanin mutum.

8. Duk mutumin da ya kafirce wa Alƙur’ani, to kowane irin matsayi zai samu a duniya, shi a wurin Allah ba kowa ba ne, hasararre ne.

Suratul Baƙara (120-123)

وَلَن تَرۡضَىٰ عَنكَ ٱلۡيَهُودُ وَلَا ٱلنَّصَٰرَىٰ حَتَّىٰ تَتَّبِعَ مِلَّتَهُمۡۗ قُلۡ إِنَّ هُدَى ٱللَّهِ هُوَ ٱلۡهُدَىٰۗ وَلَئِنِ ٱتَّبَعۡتَ أَهۡوَآءَهُم بَعۡدَ ٱلَّذِي جَآءَكَ مِنَ ٱلۡعِلۡمِ
مَا لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٍ ١٢٠ ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَتۡلُونَهُۥ حَقَّ تِلَاوَتِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۗ وَمَن يَكۡفُرۡ بِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ
ٱلۡخَٰسِرُونَ ١٢١ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتِيَ ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ وَأَنِّي فَضَّلۡتُكُمۡ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٢٢ وَٱتَّقُواْ يَوۡمٗا لَّا تَجۡزِي نَفۡسٌ عَن
نَّفۡسٖ شَيۡـٔٗا وَلَا يُقۡبَلُ مِنۡهَا عَدۡلٞ وَلَا تَنفَعُهَا شَفَٰعَةٞ وَلَا هُمۡ يُنصَرُونَ ١٢٣

120. Yahudawa da Nasara ba za su taɓa yarda da kai ba har sai ka bi addininsu. Ka ce: “Shiriyar Allah lalle ita ce shiriya”. Idan har ka bi son zuciyarsu bayan abin da ya zo maka na gaskiya, to ba ka da wani majiɓinci ko mai taimakonka wajen Allah.

121. Waɗanda Muka saukar musu da littafi suna karanta shi yadda ya cancanta a karanta shi, waɗannan su ne suke yin imani da shi. Kuma waɗanda suka kafirce masa to waɗannan su ne hasararru.

122. Ya ku Banu Isra'ila, ku tuna ni'imar da Na yi muku, kuma lalle Ni Na fifita ku a kan talikai (na zamaninku).

123. Kuma ku kiyayi wani yini da wani rai ba zai isar wa da wani rai komai ba, kuma ba za a karɓi wata fansa daga gare shi ba, kuma ceto ba zai amfane shi ba, kuma su ba za a taimaka musu ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa ma'abota littafi ba za su taɓa yarda da shi ba, har sai ya bi addininsu, domin suna ganin su ne a kan gaskiya, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa irin martanin da ya kamata ya mayar musu, ya ce: "Shiriya ta gaskiya ita ce shiriyar Allah," wadda ya zo da ita daga Ubangijinsa, watau addinin Musulunci.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da gargaɗin Annabinsa har ma da al'ummarsa, da kada su kuskura, ko da wasa su bi son zukatan ma'abota littafi, bayan Allah ya ɗaukaka su da falalar ilimi, wanda shi ne abin da aka yi wa Annabinsa (ﷺ) wahayi da shi na Alƙur'ani, mai rabewa tsakanin ƙarya da gaskiya, yake bambancewa tsakanin ɓata da shiriya da tsakanin kafirci da imani. Kuma ya yi masa gargaɗi da cewa, idan har ya kuskura ya bi son zuciyarsu, to zai rasa mai jiɓintar lamarinsa ya janyo masa wani alheri, ko wanda zai taimaka masa ya kare shi daga wani sharri.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi duk wani ma'abocin littafi wanda ya rungumi Littafin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya karanta shi, ya yi aiki da koyarwarsa bayan ya fahince shi, bai canza wani abu daga cikin ma'anoninsa ko ya gurɓata karantarwarsa ba, to wannan mumini ne na gaskiya, kuma imaninsa zai taimaka masa wajen ba da gaskiya da Annabi (ﷺ), domin zai ga yadda Littafinsa ya faɗi siffofin Annabi (ﷺ), kuma ya yi kira da a yi imani da shi duk sa'adda ya bayyana. To amma daga cikinsu, duk wanda ya kafirce wa Littafinsa, ta hanyar canza shi da jirkita ma'anonisa da kafirce wa Annabi (ﷺ), to masu irin waɗannan siffofi su ne hasararru duniya da lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da Banu Isra'ila ni'imar da ya yi musu, wato wadda ya yi wa kakanninsu, ya fifita su a kan sauran al'ummomin zamaninsu, ya ba su sarauta, ya aiko musu da annabawa da yawa daga cikinsu. To wanda ya yi musu irin waɗannan ni'imomi, ai ya wajaba su gode masa ta hanyar shiga addininsa, da imani da Manzon da ya aiko. Daga ƙarshe Allah ya sake jan hankalinsu da su kiyayi gamuwarsu da azabar ranar lahira ta hanyar aiwatar da abin da ya wajaba a kansu, da barin abin da aka hana su, don su kare kansu daga azabar wannan yini, wanda babu wani mahaluƙi da zai iya taɓuka wa ɗan uwansa da komai, komai irin dangantakarsu, kuma komai ƙanƙantar wannan abu, kamar yadda babu wanda zai iya fansar wani a ranar daga azabar Allah, kuma babu wani kafiri da zai sami ceto a wannan ranar ko a kuɓutar da shi daga azabar Allah mai raɗaɗi.

Daga waɗannan ayoyi za mu ƙaru da abubuwa kamar haka:

1. Ana cancantar shugabanci na addini ne ta hanyar tsoron Allah da aiki na ƙwarai, ba ta hanyar gado daga iyaye ba.

2. Idan mutum ya bi umarnin Allah, sai Allah ya yi masa sakamako fiye da aikinsa, kamar yadda ya saka wa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da shugabancin mutane gaba ɗaya ta fuskar addini da mayar da wurin tsayuwarsa wurin yin salla bayan ya cika umarnin da Allah ya yi masa.

3. Adalci yana ɗaya daga cikin rukunan cancantar shugabancin al'umma, duk wani azzalumi bai dace da shugabanci ba.

4. Zaman lafiya a gari da samuwar wadatar arziki suna daga cikin abubuwan da sukan taimaka wajen bauta wa Allah yadda ya kamata, shi ya sa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fara

da roƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa mutanen Makka baiwa da su, kamar yadda yake a nan da kuma *Suratu Ibrahim*, aya ta 35.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayar da ni'imarsa ta duniya ga Musulmi da kafiri da mutum da dabba, ba tare da sharɗanta imaninsa ba. Amma a lahira Allah ya keɓance ni'imarsa ne ga muminai kawai.

6. Abin da duk Allah zai ba wa kafiri na ni'ima a nan duniya, komai yawansa, to ɗan jin daɗi ne taƙaitacce, domin bayan mutuwa zai gamu da wata azaba marar yankewa a lahira. Annabi (ﷺ) yana cewa, "Allah yana iya yi wa azzalumi talala har lokacin da zai kama shi, ba zai iya kuɓuce masa ba." [Bukhari #4685, da Muslim #2583].

7. Babban muhimmin al'amari a wajen mumini shi ne Allah ya karɓi aikinsa na ƙwarai. Don haka kada ya ruɗu da yawan ayyukansa na alheri, ya dai yi ta addu'ar Allah ya karɓa masa.

8. Ba a yarda mutum ya bauta wa Allah ba sai da abin da ya yi umarni da shi kuma Annabinsa (ﷺ) ya koyar. Shi ya sa Annabi Ibrahim da Annabi Isma'il suka yi addu'a da cewa, "Kuma ka nuna mana ayyukan ibadunmu."

9. Addu'ar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara karɓarta, yana karɓar ta komai daɗewa. Allah bai tabbatar da addu'ar Annabi Ibrahimu da ɗansa Annabi Isma'il ba sai bayan shuɗewar shekaru masu tarin yawa, lokacin da ya aiko Annabinsa (ﷺ).

10. Yana da kyau idan mutum ya gyaru a karan kansa, to ya yi ƙoƙari ya ga wasu ma sun gyaru, don haka Annabi Ibrahim da ɗansa Isma'il suka riƙa addu'ar Allah ya aiko da wani manzo mai karantarwa a cikin zurriyarsu a bayansu.

11. Kula da tarbiyyar 'ya'ya da addininsu wajibi ne a kan iyaye.

12. Girman sha'anin aƙida a wajen annabawa, don haka suke jaddada wa 'ya'yansu batunta har a cikin yanayin mutuwa, domin su sami nutsuwar zuciya game da makomar 'ya'yansu ta fuskar aƙida a bayansu.

13. Duk waɗanda za su saba wa karantarwar annabawa, to waɗannan wawaye ne, marasa sanin ciwon kansu, ko da kuwa a zahiri ana ganin su wayayyu.

Suratul Baƙara (124-134)

* وَإِذِ ٱبۡتَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ رَبُّهُۥ بِكَلِمَٰتٖ فَأَتَمَّهُنَّۖ قَالَ إِنِّي جَاعِلُكَ لِلنَّاسِ إِمَامٗاۖ قَالَ وَمِن ذُرِّيَّتِيۖ قَالَ لَا يَنَالُ عَهۡدِي ٱلظَّٰلِمِينَ ١٢٤ وَإِذۡ جَعَلۡنَا ٱلۡبَيۡتَ مَثَابَةٗ لِّلنَّاسِ وَأَمۡنٗا وَٱتَّخِذُواْ مِن مَّقَامِ إِبۡرَٰهِـۧمَ مُصَلّٗىۖ وَعَهِدۡنَآ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ أَن طَهِّرَا بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡعَٰكِفِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ ١٢٥ وَإِذۡ قَالَ إِبۡرَٰهِـۧمُ رَبِّ ٱجۡعَلۡ هَٰذَا بَلَدًا ءَامِنٗا وَٱرۡزُقۡ أَهۡلَهُۥ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ مَنۡ ءَامَنَ مِنۡهُم بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۖ قَالَ وَمَن كَفَرَ فَأُمَتِّعُهُۥ قَلِيلٗا ثُمَّ أَضۡطَرُّهُۥٓ إِلَىٰ عَذَابِ ٱلنَّارِۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ١٢٦ وَإِذۡ يَرۡفَعُ إِبۡرَٰهِـۧمُ ٱلۡقَوَاعِدَ مِنَ ٱلۡبَيۡتِ وَإِسۡمَٰعِيلُ رَبَّنَا تَقَبَّلۡ مِنَّآۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ١٢٧ رَبَّنَا وَٱجۡعَلۡنَا مُسۡلِمَيۡنِ لَكَ وَمِن ذُرِّيَّتِنَآ أُمَّةٗ مُّسۡلِمَةٗ لَّكَ وَأَرِنَا مَنَاسِكَنَا وَتُبۡ عَلَيۡنَآۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ١٢٨ رَبَّنَا وَٱبۡعَثۡ فِيهِمۡ رَسُولٗا مِّنۡهُمۡ يَتۡلُواْ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِكَ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَيُزَكِّيهِمۡۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١٢٩ وَمَن يَرۡغَبُ عَن

مِّلَّةِ إِبۡرَٰهِـۧمَ إِلَّا مَن سَفِهَ نَفۡسَهُۥۚ وَلَقَدِ ٱصۡطَفَيۡنَٰهُ فِي ٱلدُّنۡيَاۖ وَإِنَّهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١٣٠ إِذۡ قَالَ لَهُۥ رَبُّهُۥٓ أَسۡلِمۡۖ قَالَ أَسۡلَمۡتُ لِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٣١ وَوَصَّىٰ بِهَآ إِبۡرَٰهِـۧمُ بَنِيهِ وَيَعۡقُوبُ يَٰبَنِيَّ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصۡطَفَىٰ لَكُمُ ٱلدِّينَ فَلَا تَمُوتُنَّ إِلَّا وَأَنتُم مُّسۡلِمُونَ ١٣٢ أَمۡ كُنتُمۡ شُهَدَآءَ إِذۡ حَضَرَ يَعۡقُوبَ ٱلۡمَوۡتُ إِذۡ قَالَ لِبَنِيهِ مَا تَعۡبُدُونَ مِنۢ بَعۡدِيۖ قَالُواْ نَعۡبُدُ إِلَٰهَكَ وَإِلَٰهَ ءَابَآئِكَ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ إِلَٰهٗا وَٰحِدٗا وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ١٣٣ تِلۡكَ أُمَّةٞ قَدۡ خَلَتۡۖ لَهَا مَا كَسَبَتۡ وَلَكُم مَّا كَسَبۡتُمۡۖ وَلَا تُسۡـَٔلُونَ عَمَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٣٤

124. Kuma ka tuna lokacin da Ubangijin Ibrahimu Ya jarrabe shi da wasu kalmomi, sai ya cika su, sai ya ce: “Ni zan naɗa ka shugaba ga mutane”. Sai (Ibrahimu) ya ce: “Har da kuma zurriyata”; Sai (Allah) Ya ce: “Alƙawarina ba zai shafi azzalumai ba.”

125. Kuma ka tuna lokacin da Muka sanya wannan Ɗaki ya zama matattara ga mutane da kuma aminci; kuma ku mayar da *Maƙamu Ibrahim wajen* salla; kuma Muka yi umarni ga Ibrahim da Isma'ila da cewa: “Ku tsarkake Ɗakina don masu ɗawafi da masu i'itikafi da masu ruku'u da sujjada”.

126. Kuma ka tuna lokacin da Ibarhimu ya ce: “Ya Ubangijina, Ka sanya wannan (wuri) ya zama gari mai aminci, kuma Ka arzuta mutanensa da kayan marmari, (amma) wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira daga cikinsu”. Sai (Allah) Ya ce: “Har ma wanda ya kafirta, zan jiyar da shi daɗi kaɗan, sannan in tilasa masa shiga azabar wuta, tir da wannan makoma.”

127. Kuma ka tuna lokacin da Ibrahimu yake ɗaga harsashen ginin Ɗakin Ka'aba tare da Isma'ila, suna cewa: “Ya Ubangijinmu Ka karɓa mana; lalle Kai Mai ji ne Mai gani.”

128. “Ya Ubangijinmu, Ka sanya mu masu miƙa wuya gare Ka, kuma a cikin zurriyarmu ma (Ka samar) da wata al'umma mai miƙa wuya gare Ka, kuma Ka nuna mana ayyaukan ibadarmu, kuma Ka karɓi tubanmu, lalle Kai Mai yawan karɓar tuba ne Mai jin ƙai.”

129. “Ya Ubangijinmu, Ka aiko da wani manzo daga cikinsu, da zai riƙa karanta musu ayoyinka, kuma yana koyar da su Littafi da hikima, kuma ya riƙa yi musu tarbiyya. Lalle kai Mabuwayi ne, Mai hikima.”

130. Babu kuma wanda zai ƙi addinin Ibrahimu sai wanda bai san ciwon kansa ba. Kuma haƙiƙa Mun zaɓe shi a duniya, kuma shi a lahira yana cikin mutanen ƙwarai.

131. Ka tuna lokacin da Ubangjijinsa Ya ce masa: “Ka miƙa wuya”, sai ya ce: “Na miƙa wuya ga Ubangijin talikai.”

132. Kuma Ibrahimu da Ya'aƙubu suka yi wasiyya da wannan ga 'ya'yansu cewa: “Ya 'ya'yana, lalle Allah Ya zaɓa muku addini, don haka kada ku mutu face kuna Musulmi.”

133. Ko kuna nan ne lokacin da mutuwa ta zo wa Yaƙubu, lokacin da ya ce wa 'ya'yansa: “Me za ku bauta wa a bayana?” Sai suka ce: “Za mu bauta wa abin bautarka kuma abin bautar iyayenka, Ibarhimu da Isma'ila da Ishaƙa, abin bauta guda ɗaya, kuma mu gare Shi muke miƙa wuya.”

134. Waccan al'umma ce da ta riga ta wuce; abin da ta aikata mallakarta ne, ku ma abin da kuka aikata naku ne, kuma ba za a tambaye ku ba game da abin da suka kasance suna aikatawa.”

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tuna wa Banu Isra'ila wasu daga cikin ni'imomin da ya yi musu a baya da irin yadda suka ƙalubalanci waɗannan ni'imomin ta hanyar butulci da kafirci da ƙaryata annabawa da ma kashe wasunsu, ya kuma bayyana irin cika baki da gadara da suka riƙa nunawa na cewa, su ne zaɓaɓɓu a wurin Allah, babu mai shiga Aljanna in ba su ba, da dai sauran ire-iren waɗannan maganganu nasu na soki-burutsu, sai Allah Ta'ala ya kawo wani ɓangare na tarihin Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), mahaifin Annabi Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Ishaƙa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kuma kakan Annabi Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), domin ya rushe abin da Yahudawa da Nasara da mushirikan Larabawa suke yaɗawa na alaƙarsa da gurɓataccen addinansu. Kuma ta ɓangare guda ya bayyana ƙaƙƙarfar alaƙarsa shi da 'ya'yansa da addinin Musulunci da kuma Ɗakin Ka'aba wanda Allah ya umarce shi da ginawa don ya zama wata alama ce ta zahiri da kaɗaitar Allah da bauta, wato Tauhidi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tuna wa Annabinsa (ﷺ) irin jarrabawar da ya yi wa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ta hanyoyi daban-daban, waɗanda suka shafi umarni da hani, da sauran hukunce-hukunce na shari'a da kuma wasu al'amura da ya jarrabe shi da su na rayuwa, kamar ƙiyayyar da mutanensa suka nuna masa, har suka yi yunƙurin ƙona shi ƙurmus da wuta da umarnin da Allah ya yi masa na ya yanka ɗansa Isma'il, ya kuma sallama wa wannan umarni, daga bisani sai Allah ya fanshe shi da wani abin yanka babba. Duk kuma ire-iren waɗannan jarrabobi da Allah ya yi masa, ya cinye su cib-cib. To daga nan sai Allah ya sanar da shi cewa, ya zaɓe shi ya zama Shugaba abin koyi ga mutane. Jin haka sai Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka)

da ya sanya wannan shugabancin na addini a cikin zurriyyarsa da za su zo bayansa. Sai Allah ya amsa masa da cewa, shugabanci na addini ba zai taɓa shiga hannun azzalumi ba, don haka ya janye wannan buƙata tashi. Allah kuwa ya cika wa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wannan alƙawari, kamar yadda ya faɗa a cikin *Suratul Hadid*, aya ta 26.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tuna wa Annabi (ﷺ) irin ɗaukakar da ya yi wa Ɗakinsa mai alfarma na Makka, yadda ya kimsa soyayyarsa a cikin zukatan mutane, suna ta marmarin ziyarar sa babu ƙaƙƙautawa, ko sau nawa ɗayansu zai je ziyarar sa ba ya ginsar sa ko ya ƙosa da ganin sa. Bayan haka kuma ya mayar da shi wuri mai aminci ga rayukan jama'a da dukiyarsu, kai amincinsa ya kai har ga dabbobi da itatuwa, ta yadda ba a farauta a cikin haraminsa, kuma ba a cire itatuwan cikinsa, kamar yadda ya zo a hadisan Annabi (ﷺ). [Duba Bukhari #2129, da Muslim #1362].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da al'ummarsa da su riƙi wurin tsayawar Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zama wurin salla. Dalilin saukar wannan gaɓa ta ayar yana cikin Hadisin da Imamul Bukhari ya ruwaito daga Umar ɗan Khaɗɗab, yana cewa: "Na dace da (hukuncin) Ubangijina cikin abubuwa guda uku. Na ce, ina ma da a ce za mu mayar da wurin tsayuwar Annabi Ibrahim wajen salla, sai ko aka saukar da faɗar Allah: "Kuma ku mayar da Maƙamu Ibrahim wajen salla." [Bukhari #412]. Don haka ya zamo sunnar mai yin ɗawafi, yayin da ya gama ɗawafinsa zagaye bakwai, ya je bayan Muƙamu Ibrahim ya yi salla raka'a biyu ya karanta *Suratul Ikhlas*i da *Suratul Kafirun*, kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya yi. [Muslim #1218].

Wasu malaman tarihi sun fassara ma'anar *Muƙamu Ibrahim* da cewa, ana nufin wuraren da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tsaya lokacin aikin Hajji. Don haka a wannan ayar ana umartar Musulmi ne, mahajjata su yi koyi da shi wajen tsayuwa da ibada da addu'a a waɗannan wurare yayin aikin hajjinsu. Salla raka'a biyu bayan gama ɗawafi kuma ta shiga ciki.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa ya yi umarni mai ƙarfi ga Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da su tsabtace ɗakinsa daga shirka da kafirci da gumaka da ƙazanta, domin masu ɗawafi da masu zama cikinsa domin ibada, da masallata a cikinsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya labarta mana addu'a da ƙoƙon-barar da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gabatar wa Ubangijinsa, yana neman da ya arzuta mazauna garin

Makka da zaman lafiya na dindindin, sannan ya hore wa muminai daga cikinsu abin da za su ci. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa masa cewa, arziki a duniya Allah yana bayar da shi ga kowa ne, mumini da kafiri, bai taƙaita a kan muminai su kaɗai ba. To sai dai abin da Allah zai ba wa kafiri na arziki a nan duniya, komai yawansa ɗan kaɗan ne idan aka kwatanta shi da ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadar wa masu imani a ranar lahira. Sannan shi kuma wanda ya kafirta, Allah zai jefa shi wutar Jahannama, wadda makoma ce mai munin gaske.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba wa Annabinsa (ﷺ) labarin lokacin da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Isma'il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka sanya harsashin ginin Ɗakin Ka'aba, don su ɗaga ta ta zama cikakken ɗaki, sanda suke ɗaga hannayensu suna addu'a Allah ya karɓa musu wannan aiki nasu, kuma Allah yana jin addu'arsu, kuma yana sane da aikinsu da kyakkyawar niyyarsu. Hakanan suka roƙe shi da ya sanya su su zama har ko da yaushe masu miƙa wuya ne da ƙaskantar da kai gare shi da sallama wa umarninsa. Kuma suka roƙe shi da ya samar da wata al'umma mai miƙa wuya ga umarninsa a cikin zurriyyarsu. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karɓa duk waɗannan addu'o'i nasu gaba ɗaya.

Hakanan cikin addu'o'insu sun roƙe shi ya bayyana musu wuraren ibadunsu, musamman ibadar Hajji, kuma ya datar da su ga tuba, sannan ya karɓi tuban nasu, domin shi ne mai karɓar tuba, mai rahama ga wanda ya so daga cikin bayinsa. Hakanan suka roƙe shi da ya aiko da wani Manzo daga cikin zurriyarsu Larabawa, wanda zai riƙa karanta musu Littafin Allah, yana koyar da su ilimin Alƙur'ani da Sunna, kuma yana yi musu tarbiyya ta zuci da ta halaye. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya karɓi wannan addu'a tasu, ya aiko da Annabi Muhammad (ﷺ) daga cikin ƙabilar Kuraishawa, gidan Banu Hashim, masu dangantaka da Annabi Isma'i (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ɗan Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Don haka ne Annabi (ﷺ) yake cewa: "Ni addu'ar Babana ne Ibrahim." [Ahmad #2261].

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gama magana a kan Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ɗansa Isma'ila, da yadda suka gina Ɗakin Allah, Ka'aba da umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sai ya bayyana cewa, babu wanda zai ƙyamaci kasancewa ɗaya daga cikin mabiya addinin da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo da shi na kaɗaita Allah da bauta masa sai mutumin da yake wawa, wanda bai san ciwon kansa ba, domin Allah ya zaɓi Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya ba shi annabci da manzanci da shugabanci na addini, sannan kuma a lahira yana cikin ayarin mutanen kirki, masu samun babban rabo. Domin bayan Allah ya zaɓe shi a nan duniya, to ya umarce shi da ya miƙa wuya, ya sallama wa Ubangijinsa komai, kuma nan take ya amsa, ya miƙa wuyansa ga Ubangijin talikai, ya tsarkake addininsa gare shi shi kaɗai, ba tare da haɗa shi da komai ba. Haka kuma Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wasiyya da wannan umarni na Allah ga 'ya'yansa cewa, su riƙi wannan addini, kada su yi wasa da shi har mutuwarsu ta zo musu suna kai, domin duk wanda ya rayu a kan abu, to zai mutu ne a kansa. Hakanan shi ma jikansa Yakubu ya yi wasiyya irin wannan ga 'ya'yansa.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya juyar da akalar tambaya zuwa ga Yahudawa masu ƙaryata Annabi Muhammadu (ﷺ) cewa, shin sun halarci lokacin da Annabi Yaƙubu kakansu mutuwa ta zo masa, ya tara 'ya'yansa yana tambayar su, me za su bauta wa bayan mutuwarsa? Sai suka amsa masa da cewa, za su bauta wa abin bautarsa, kuma abin bautar iyayensa, waɗanda suka haɗa da kakansa Annabi Ibrahim, da baffansa Annabi Isma'il, da kuma babansa Annabi Ishaƙa. Dukkaninsu abin bautarsu ɗaya ne, wanda ya cancanci a bauta masa shi kaɗai ba tare da an haɗa shi da komai ba, shi ne Allah. Suka shelanta masa cewa, duk gaba ɗayansu sun miƙa wuya ne gare shi da ƙaskantar da kai wajen bauta masa.

Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rufe wannan batu da kiran Yahudawa da Nasara cewa, su manta da maganar alfahari da iyayensu da kakanninsu. Kasancewarsu su zurriyarsu ne wannan kawai ba zai amfane su da komai ba a wurin Allah, domin su waɗancan al'umma ce da ta riga ta gabata, sakamakon ayyukansu su kaɗai zai shafa. Don haka su ma na zamanin Annabi (ﷺ) sai su tashi su nemi na

kansu; abin da duk suka aikata a kansa ne za a yi musu tambayoyi da hisabi a ranar alƙiyama, ba za a tambaye su ayyukan iyayensu da kakanninsu ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Maɓarnata ba za su gushe ba suna kira zuwa ga ɓatansu.

2. Addinin Musulunci daidai yake da addinin annabawa gaba ɗaya, ta fuskar kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Duk wanda ya riƙe Allah, ya dogara da shi, to zai kare shi daga sharrin duk wani mai sharri.

4. Ɓoye gaskiya bayan mutum ya san ta, ba ƙaramin laifi ba ne a wurin Allah.

5. Addinin Yahudanci da na Kiristanci suna ƙunshe da shirka, don haka ba za su taɓa zama addinan Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shugaban masu Tauhidi ba.

6. Ayyukan ma'abota littafi na addininsu ba za su taɓa haɗuwa da irin na Musulmi ba, ballantana har a yi su tare, shi ya sa Allah ya ce: "Ayyukanmu na gare mu, ku ma ayyukanku na gare ku."

Suratul Baƙara (135-141)

وَقَالُواْ كُونُواْ هُودًا أَوۡ نَصَٰرَىٰ تَهۡتَدُواْۗ قُلۡ بَلۡ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِـۧمَ حَنِيفٗاۖ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١٣٥ قُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَمَآ أُوتِيَ ٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمۡ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ١٣٦ فَإِنۡ ءَامَنُواْ بِمِثۡلِ مَآ ءَامَنتُم بِهِۦ فَقَدِ ٱهۡتَدَواْۖ وَّإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا هُمۡ فِي شِقَاقٖۖ فَسَيَكۡفِيكَهُمُ ٱللَّهُۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ١٣٧ صِبۡغَةَ ٱللَّهِ وَمَنۡ أَحۡسَنُ مِنَ ٱللَّهِ صِبۡغَةٗۖ وَنَحۡنُ لَهُۥ عَٰبِدُونَ ١٣٨ قُلۡ أَتُحَآجُّونَنَا فِي ٱللَّهِ وَهُوَ رَبُّنَا وَرَبُّكُمۡ وَلَنَآ أَعۡمَٰلُنَا وَلَكُمۡ أَعۡمَٰلُكُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُخۡلِصُونَ ١٣٩ أَمۡ تَقُولُونَ إِنَّ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطَ كَانُواْ هُودًا أَوۡ نَصَٰرَىٰۗ قُلۡ ءَأَنتُمۡ أَعۡلَمُ أَمِ ٱللَّهُۗ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّن كَتَمَ شَهَٰدَةً عِندَهُۥ مِنَ ٱللَّهِۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ١٤٠ تِلۡكَ أُمَّةٞ قَدۡ خَلَتۡۖ لَهَا مَا كَسَبَتۡ وَلَكُم مَّا كَسَبۡتُمۡۖ وَلَا تُسۡـَٔلُونَ عَمَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٤١

135. Suka ce: "Ku zama Yahudawa ko Nasara za ku shiriya". Ka ce: "A'a! Za mu bi addinin Ibrahimu ne wanda yake miƙe totar, kuma bai zamo daga cikin masu shirka ba."

136. Ku ce: "Mun yi imani da Allah da abin da aka saukar mana, da abin da aka saukar wa Ibrahimu da Isma'ila da Ishaƙa da Yaƙubu da jikoki da abin da aka ba wa Musa da Isa da abin da aka ba annabawa duka daga Ubangijinsu, kuma ba ma nuna bambanci tsakanin wani daga cikinsu, kuma mu gare Shi muke miƙa wuya."

137. Don haka idan sun yi imani da irin abin da kuka yi imani da shi, to haƙiƙa sun shiriya, idan kuwa suka juya da baya, to haƙiƙa su suna cikin saɓani. To lalle Allah zai isar maka da su, kuma Shi Mai ji ne, Mai gani.

138. Rinin Allah, wane ne kuwa ya fi Allah kyan rini? Kuma mu masu bauta ne a gare Shi.

139. Ka ce, “Shin za ku yi jayayya da mu ne game da sha'anin Allah, alhalin Shi ne Ubangijinmu kuma Ubangijinku? Kuma ayyukanmu namu ne, ayyukanku kuma naku ne, kuma mu masu tsarkake ayyuka ne gare Shi (Allah).

140. Ko kuma kuna cewa ne, “Lalle Ibrahimu da Isma'ila da Ishaƙa da Yaƙubu da jikoki sun kasance Yahudawa ne ko Nasara?” Ka ce: “Ku ne kuka fi sani ko kuma Allah?” Kuma ba wanda ya fi zalunci kamar wanda ya ɓoye shaidar da take wajensa daga Allah, kuma Allah ba rafkananne ne ba game da abin da suke aikatawa.

141. Waccan al'umma ce da ta riga ta wuce, abin da ta aikata mallakarta ne, ku ma abin da kuka aikata naku ne, kuma ba za a tambaye ku game da abin da suka kasance suna aikatawa ba.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi mana bayanin ruɗuwa irin ta Yahudawa da Nasara ne game da wasu maganganunsu marasa kan gado da hujja. Wai kiran Annabi (ﷺ) da Musulmai suke yi cewa, su bar addininsu su zo su rungumi nasu shi ne shiriya. Yahudawa suka yi irin wannan kira zuwa ga addinin Yahudawa, Nasara ma suka yi irinsa zuwa ga Kiristanci. Sai Allah ya ce da Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, babu shiriya a cikin addininsu sam-sam; shiriya tana cikin addinin da Annabi Ibrahim ya zo da shi ne, wanda kuwa a cikinsa babu haɗa Allah da wani, sai kaɗaita Allah kawai wajen bauta. Don haka Annabi Ibrahim ba Bayahude ne ba, ba kuma Banasare ba ne, sannan ba mushiriki ba ne.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa muminai abin da kawai za su yi imani da shi shi ne, Kaɗaitakar Ubangijinsu Allah da kuma imani da duk abin da Allah ya aiko Annabinsa Muhammad (ﷺ) da shi. Haka kuma su yi imani da duk annabawan da ya aiko da littattafan da ya ba su, waɗanda ya bayyana musu sunayensu da ma waɗanda bai ambata musu komai na labarinsu ba. Su ba da gaskiya da su a dunƙule gaba ɗaya, ba tare da rarrabewa a tsakaninsu ba; saboda kafirce wa annabin Allah ɗaya daidai yake da kafirce wa dukkansu, kamar yadda ya ambata a *Suratun Nisa’i*, aya ta 150-151. Annabawan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata a wannan ayar sun haɗa da:

1. Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), uban annabawa, wanda Allah ya saukar masa da wasu littattafai da ya ambata a *Suratun Najmi*, aya ta 36-37, da kuma *Suratul A’ala*, aya ta 19.

2. Annabi Isma’il, Allah bai sanar da mu komai dangane da littattafansa ba.

3. Annabi Ishaƙ da Annabi Ya’aƙuba. Su ma Allah bai sanar da mu abin da ya saukar musu ba.

4. Jikoki, su ne annabawan da suke cikin zurriyar Annabi Ya’aƙuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin Yahudu da Nasara cewa, idan su ma suka yi imani da irin abin da muminai suka yi imani da shi, to sun zama shiryayyu, idan kuwa har suka bijire, to ya kamata su muminai su fahinci cewa, waɗannan mutane jayayya kawai suke nema da adawa da su, ba gaskiya ba. Allah ya nuna wa Manzonsa (ﷺ) cewa, kada ya damu da adawarsu da makirce-makircensu, Allah zai tsaya masa, ya ba shi kariya, ya taimake shi a kansu, domin yana jin duk abin da suke faɗa a kansa, kuma yana sane da ƙulle-ƙullensu da suke shiryawa a ɓoye. Don haka sai Allah ya umarce su da lalle su lazimci addinin Allah wanda shi ne Musulunci, kuma da shi ne Allah ya rina su, ya fito da su cikin wata kyakkyawar kama mai ban sha’awa, kuma babu wanda ya fi Allah kyan rini. Don haka su zama masu ƙasƙantar da kai a gare shi masu bauta masa shi kaɗai.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya kira Yahudawa da Nasara waɗanda suke jayayya da muminai ba tare da gaskiya ba, ya faɗa musu cewa, yanzu ta yaya za su riƙa

jayayya da muminai a kan sha'anin Tauhidi da miƙa wuya ga umarnin Allah, ko kuma a kan abin da Allah ya keɓanci Annabi (ﷺ) da shi tare da al'ummarsa, na fifita shi a kan sauran annabawa da fifita al'ummarsa a kan sauran al'ummomi? Da me suka dogara da shi na ganin su ne suka fi cancantar wannan matsayi, tare da cewa su duka Allah ne Ubangijinsu, kuma shi ne mai yin yadda ya ga dama. Kuma me zai sa su ya ba su, su kuma Musulmi ya hana su? Idan har shi ne yake ganin dama ya ba wa wanda yake so, to babu dalilin da zai sa su ce ba zai yi wa muminai baiwa ba, don su ma shi ne Ubangijinsu. Idan kuma ayyukansu ne suka sa Allah ya ba su abin da suke riyawa, to ai su ma muminai suna da nasu ayyukan waɗanda suka fi nasu kyau, domin su muminai suna tsarkake shi da bauta, saɓanin su da suke yin shirka. Idan kuwa haka ne, to su muminai su suka fi su cancantar wannan baiwar tasa.
Daga nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ƙaryar da Yahudawa da Nasara suke yi na cewa, Annabi Ibrahim da 'ya'yansa sun kasance a kan addinin Yahudanci ko Kiristanci, tare da cewa, waɗannan addinai ne da suka zo bayan shuɗewar waɗannan annabawa. To ta yaya kuma za a danganta su da waɗannan addinai biyu? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa (ﷺ) ya tambaye su: Shin su ne suka fi Allah sanin halin da manzannin suka kasance a kai? Babu shakka amsar ɗaya ce, Allah ne mafi sani. To idan haka ne, me ya sa suke ɓoye wannan shaidar, ba za su bayar da ita ba? Tabbas babu azzalumi kamar wanda zai ɓoye shaidar wajensa wadda daga Allah take. To irin waɗannan mutane su kwana da sanin cewa, Allah yana sane da duk abin da suke aikatawa, kuma zai yi musu sakayya a kai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma a nan ya sake jaddada musu waccan magana da ya yi musu a baya cewa, su daina alfahari da iyayensu da kakanninsu da ayyukan da suka yi, wannan ba zai amfane su da komai ba, domin sakamakon waɗannan ayyuka za su taƙaita ne a kan masu su. Don haka su ma za a yi musu hisabi ne da sakamako a kan ayyukansu na alheri ko na sharri, ba za a tambaye su komai game da ayyukan iyayensu da kakanninsu ba.

Daga waɗannan ayoyin za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake kwantar wa da Annabinsa (ﷺ) hankali, ya ba shi labarin maganar da maƙiyansa za su faɗa masa game da lamarin canza alƙibla tun gabanin faruwarta.

2. Duk wanda zai riƙa jayayya da shari'ar Allah da Manzonsa, to wannan wawa ne, marar hankali.

3. Al'ummar Annabi (ﷺ) ta fi kowace al'umma da aka taɓa yi a bayan ƙasa, saboda zaɓin da Allah ya yi mata, ya aiko da Annabinsa Muhammadu (ﷺ) a cikinta.

4. Sahabban Annabi (ﷺ) dukkansu adalai ne, domin wannan aya ta fi gaskata a kansu, fiye da duk wani da zai zo bayansu.

5. Ba wanda ake karɓar shaidarsa sai adali.

6. Haƙiƙanin ci gaba shi ne biyayya ga Annabi (ﷺ), duk wanda ba ya yi masa biyayya to ya ci baya.

7. Ayyukan ɗa'a duka suna ƙarƙashin ma'anar 'imani', don haka Allah ya kira salla da sunan imani.

8. Tabbatar da ɗaukakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a kan halittunsa, don haka Annabi (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ɗaga kansa sama yayin roƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya canza alƙibla.

9. Aiki da hukunce-hukuncen shari'a abu ne mai nauyin gaske ga mutanen da ba su da cikakken imani da shiriya a zukatansu.

10. Ɗora Musulmi gaba ɗayansu a kan alƙibla ɗaya babbar ishara ce zuwa ga girman lamarin haɗin kai a rayuwar Musulmi.

11. Da yawa daga cikin Yahudawa da Nasara ba rashin sanin haƙiƙanin Musulunci ne ya sa suke nuna masa ƙiyayya ba, a'a, hassada ce kawai ta cika musu zukata.

12. Duk wanda ya ƙi bin shiriyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to ko shakka babu zai bi son zuciyarsa ne, babu wata hanya ta uku.

13. Ba a kama mutum da laifi, har sai an bayyana masa hujja a ilimance.

14. Aiki da umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da tsoron sa, hanya ce ta samun shiriya daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Baƙara (142-150)

۞ سَيَقُولُ ٱلسُّفَهَآءُ مِنَ ٱلنَّاسِ مَا وَلَّىٰهُمۡ عَن قِبۡلَتِهِمُ ٱلَّتِي كَانُواْ عَلَيۡهَاۚ قُل لِّلَّهِ ٱلۡمَشۡرِقُ وَٱلۡمَغۡرِبُۚ يَهۡدِي مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ١٤٢ وَكَذَٰلِكَ جَعَلۡنَٰكُمۡ أُمَّةٗ وَسَطٗا لِّتَكُونُواْ شُهَدَآءَ عَلَى ٱلنَّاسِ وَيَكُونَ ٱلرَّسُولُ عَلَيۡكُمۡ شَهِيدٗاۗ وَمَا جَعَلۡنَا ٱلۡقِبۡلَةَ ٱلَّتِي كُنتَ عَلَيۡهَآ إِلَّا لِنَعۡلَمَ مَن يَتَّبِعُ ٱلرَّسُولَ مِمَّن يَنقَلِبُ عَلَىٰ عَقِبَيۡهِۚ وَإِن كَانَتۡ لَكَبِيرَةً إِلَّا عَلَى ٱلَّذِينَ هَدَى ٱللَّهُۗ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُضِيعَ إِيمَٰنَكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِٱلنَّاسِ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ ١٤٣ قَدۡ نَرَىٰ تَقَلُّبَ وَجۡهِكَ فِي ٱلسَّمَآءِۖ فَلَنُوَلِّيَنَّكَ قِبۡلَةٗ تَرۡضَىٰهَاۚ فَوَلِّ وَجۡهَكَ شَطۡرَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۚ وَحَيۡثُ مَا كُنتُمۡ فَوَلُّواْ وُجُوهَكُمۡ شَطۡرَهُۥۗ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ لَيَعۡلَمُونَ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّهِمۡۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا يَعۡمَلُونَ ١٤٤ وَلَئِنۡ أَتَيۡتَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ بِكُلِّ ءَايَةٖ مَّا تَبِعُواْ قِبۡلَتَكَۚ وَمَآ أَنتَ بِتَابِعٖ قِبۡلَتَهُمۡۚ وَمَا بَعۡضُهُم بِتَابِعٖ قِبۡلَةَ بَعۡضٖۚ وَلَئِنِ ٱتَّبَعۡتَ أَهۡوَآءَهُم مِّنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلۡعِلۡمِ إِنَّكَ إِذٗا لَّمِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٤٥ ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَعۡرِفُونَهُۥ كَمَا يَعۡرِفُونَ أَبۡنَآءَهُمۡۖ وَإِنَّ فَرِيقٗا مِّنۡهُمۡ لَيَكۡتُمُونَ ٱلۡحَقَّ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٤٦ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡمُمۡتَرِينَ ١٤٧ وَلِكُلِّ وِجۡهَةٌ هُوَ مُوَلِّيهَاۖ فَٱسۡتَبِقُواْ ٱلۡخَيۡرَٰتِۚ أَيۡنَ مَا تَكُونُواْ يَأۡتِ بِكُمُ ٱللَّهُ جَمِيعًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١٤٨ وَمِنۡ حَيۡثُ خَرَجۡتَ فَوَلِّ وَجۡهَكَ شَطۡرَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۖ وَإِنَّهُۥ لَلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ١٤٩ وَمِنۡ حَيۡثُ خَرَجۡتَ فَوَلِّ وَجۡهَكَ شَطۡرَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۚ وَحَيۡثُ مَا كُنتُمۡ فَوَلُّواْ وُجُوهَكُمۡ شَطۡرَهُۥ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَيۡكُمۡ حُجَّةٌ إِلَّا ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنۡهُمۡ فَلَا تَخۡشَوۡهُمۡ وَٱخۡشَوۡنِي وَلِأُتِمَّ نِعۡمَتِي عَلَيۡكُمۡ وَلَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ١٥٠

142. Da sannu wawayen mutane za su ce: "Mene ne ya sa su juyawa su bar alƙibilar da a da suke a kanta?" Ka ce: "Gabas da yamma na Allah ne, Yana shiryar da wanda Ya ga dama zuwa ga tafarki madaidaici."

143. Kamar haka ne Muka sanya ku al'umma tsaka-tsaki (zaɓaɓɓu) don ku zamo masu shaida ga mutane, kuma Manzo ya zamo mai shaida a gare ku. Kuma ba Mu sanya alƙiblar da ka kasance a kanta ba sai don Mu bayyana wanda yake biyayya ga Manzo da wanda zai ja da baya (ya bijire). Kuma lalle wannan babban lamari ne sai dai ga waɗanda Allah Ya shiryar. Kuma Allah ba zai taɓa tozarta imaninku ba. Lalle Allah Mai tausayi ne, Mai jin ƙai ga mutane.

144. Haƙiƙa Mun ga jujjuyawar fuskarka zuwa sama, to lalle za Mu fuskantar da kai zuwa ga alƙibilar da za ka yarda da ita. Don haka ka juyar da fuskarka wajajen Masallaci mai alfarma; ku ma (Musulmi) a duk inda kuke to ku juyar da fuskokinku wajajensa. Lalle kuma waɗanda aka ba su Littafi suna sane da cewa, lalle shi (wannan canji) gaskiya ne daga Ubangijinsu. Kuma Allah ba rafkananne ba ne game da abin da suke aikatawa.

145. Lalle kuma da za ka kawo wa waɗanda aka ba su Littafi kowace irin hujja ba za su bi alƙibilarka ba; kuma kai ma ba mai bin alƙibilarsu ba ne; kuma sashinsu bai zama mai bin alƙibilar sashi ba. Kuma haƙiƙa idan har ka bi soye-soyen zukatansu bayan abin da ya zo maka na gaskiya, to lalle idan ka yi haka tabbas kana cikin azzalumai.

146. Waɗanda Muka ba su Littafi suna sane da shi (Manzon Allah) kamar yadda suke sane da 'ya'yansu; kuma lalle wani ɓangare daga cikinsu tabbas suna ɓoye gaskiya alhalin suna sane.

147. Gaskiya kam daga Ubangijinka take, don haka lalle kada ka zama daga cikin masu shakka.

148. Kuma kowane ɓangare yana da inda ya sa gaba, don haka sai ku yi gaggawar cim ma alheri. A duk inda kuke Allah zai zo da ku gaba ɗaya. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai.

149. Ko ta ina ka fito, to ka juyar da fuskarka wajajen Masallaci mai alfarma; kuma lalle shi gaskiya ne daga Ubangijinka. Kuma Allah bai zama gafalalle game da abin da kuke aikatawa ba.

150. Kuma duk inda ka fita, to ka juyar da fuskarka wajajen Masallaci mai alfarma. Ku ma duk inda kuke to ku juyar da fuskokinku wajajensa, don kada ya zama mutane suna da wata hujja a kanku, sai dai waɗanda suka yi zalunci daga cikinsu, don haka kada ku ji tsoron su, ku ji tsorona, kuma domin in cika muku ni'imata, don ku shiriya.

A waɗannan ayoyi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin batun canza alƙiblar Musulmi daga kallon Baitul Maƙdis zuwa fuskantar Ɗakin Ka’aba. Annabi (ﷺ) shi da sauran Musulmai sun kasance, yayin zamansu a Makka, suna fuskantar Baitul Maƙdis ne lokutan ibadarsu. Bayan sun yi hijira zuwa Madina da kimanin wata goma sha shida zuwa sha bakwai ma Baitul Maƙdis suke fuskanta. A daidai wannan lokaci kuma Annabi (ﷺ) yana ta addu’a, yana roƙon Allah, Allah ya canza masa alƙibla ta koma ana fuskantar Ka’aba. To sai ko Allah ya karɓi addu’arsa, ya umarce shi, tare da sauran Musulmai, da su fuskanci Ka’aba a lokutan sallolinsu. Allah ya riga ya faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, wawayen mutane cikin Yahudawa da Nasara, har ma da mushirikan Makka, za su sami wani abin magana yayin da za su ga Annabi (ﷺ) da sahabbansa sun canza alƙiblar sallarsu. Da farko mushirikai ne suka riƙa sukar Annabi (ﷺ) da cewa yana da’awar bin addinin Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), amma ba ya fuskantar Ka’aba, ɗakin da shi Annabi Ibrahim ne ya gina shi. Su kuma Yahudawa suka riƙa cika baki suna cewa, fuskantar alƙiblarsu da Annabi (ﷺ) yake yi, dalili ne mai nuna cewa addininsu shi ne gaskiya, don haka ba su da buƙatar shiga Musulunci.
Bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya canza wa Annabi (ﷺ) da sahabbansa alƙibla, sai kuma waɗannan mutane suka dawo suna sukan don me za su canza alƙiblarsu? To shi ne a nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya faɗa musu cewa, gabas da yamma da abin da yake tsakaninsu duka mallakar Allah ne, shi ne yake yin yadda yake so da kayansa, don haka yana da damar ya ba da umarnin fuskantar ko’ina. Ai bin umarninsa shi ne muhimmi, ba inda za a fuskanta ba, don haka yana shiryar da wanda ya ga dama zuwa tafarkinsa madaidaici, kuma ya yi masa ɗa’a cikin dukkan umarninsa da haninsa.

A dalilin dacen da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa wannan al'umma ta Annabi (ﷺ) ne, ya zaɓo su, ya mayar da su mafifita al'ummomi kuma adalai, domin su bayar da shaida ga annabawa da cewa, sun isar wa da al'ummominsu saƙon da Allah ya aiko su da shi. Sannan shi kansa Manzon Allah (ﷺ) ya zama shaida ga al'ummarsa a kan isar da saƙon Allah zuwa gare su, da kuma gaskiyar shaidarsu ga Annabawan Allah.

Sannan Allah ya faɗa wa Annabinsa (ﷺ) hikimar canza musu alƙibla, ita ce don tantance wanda zai yi wa Annabi (ﷺ) biyayya da wanda zai yi ridda ya bar addininsa. Ba shakka lamarin wannan canji da aka samu babba ne; ba kowa ne zai iya rungumar sa da miƙa wuya ya sallama wa hukuncin Allah ba, sai wanda Allah ya so shi da shiriya.

Yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Annabi (ﷺ) umarninsa na canza alƙibla zuwa Ka'aba, to wani mutum ya yi salla tare da Annabi (ﷺ), sannan ya fita sai ya wuce wasu mutanen Madina suna salla, amma suna fuskantar Baitul Maƙdis, sai ya faɗa musu sabon umarni da ya sauka, nan take kuwa suka juya suka fuskanci Ka'ana. [Bukhari #399 da Muslim #525].

Bayan saukar wannan umarni, sai wasu sahabbai suka riƙa tunanin makomar sallar 'yan'uwansu da suka mutu suna fuskantar Baitul Maƙdis, shin ko Allah zai karɓi waɗannan salloli, ko kuma sun rushe? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwantar musu da hankali cewa, ba wanda zai tozarta wa ladan sallarsa da ya yi lokacin da ya fuskanci Baitul Maƙdis a baya, domin Allah mai girman rahama ne ga mutane.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sanar da Annabinsa (ﷺ) cewa, ya ga yadda yake ta ɗaga kansa sama yana addu'ar Allah ya canza masa alƙiblar, tare da sa ran cewa, a ko da wane lokacin Mala'ika zai sauko don sanar da shi biyan buƙatarsa, sannan Allah ya yi masa alƙawarin cewa, zai canza masa da alƙiblar da yake so. To shi ne daga bisani Allah ya umarce shi da ya fuskanci Ka'aba a sallarsa; su ma Musulmi a duk inda suke su fuskanci nahiyar wannan ɗakin. Yahudawa da Nasara ma sun karanta a cikin littattafansu cewa, wannan Annabin da zai zo zai riƙa fuskantar Ka'aba yayin salla, kuma sun san wannan gaskiya ce daga Ubangijinsu, Allah kuma yana sane da mutanen da suka san gaskiya, amma suka take ta, har ma suka riƙa sukan ta suna sane.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara sanar da Annabinsa (ﷺ) taurin kan Yahudawa da Nasara da yadda suka ƙanƙame wa ƙarya, suka ƙi barin ta. Kuma kowace irin hujja aka zo musu da ita, ba za su saki ƙaryar ba su kama gaskiya, domin ba sun ƙi bin ta ne domin sun jahilce ta ba, a'a, sun san gaskiya, sun karanta a littattafansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce shi ma Manzon Allah (ﷺ) ba mai bin tasu alƙiblar ba ne, kuma su kansu ma'abota littafi ba sa bin alƙiblar juna, Bayahude ba ya bin ta Banasare, shi ma Banasare ba ya bin ta Bayahude.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi Annabinsa (ﷺ) da kada ya bi soye-soyen zukatan ma'abota littafi, domin idan har ya aikata hakan, bayan ilimi da ya zo masa daga Allah, to zai tsinci kansa a cikin azzalumai. Da ma kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkake Annabinsa daga aikata wani abu irin wannan. Ko da yake Allah yana yin irin wannan jan kunne ne da sunan Annabinsa (ﷺ), amma yana nufin al'ummarsa, domin su fahinci girman lamarin, su kiyaye.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Annabinsa (ﷺ) cewa, Yahudu da Nasara sun san haƙiƙanin gaskiyar annabcinsa da gaskiyar abin da yake faɗa musu na maganar Allah, ciki har da batun canza alƙibla. Domin sun karanta siffofin Annabi (ﷺ) sarai a littattafansu da Allah ya saukar, kuma sun gane shi fiye da yadda suke gane 'ya'yan cikinsu, amma saboda butulci, wasu daga cikinsu sai su riƙa ɓoye gaskiya alhalin sun san ta. Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Annabi (ﷺ) tsantsar gaskiyar da ya zo da ita daga wajen Ubangijinsa, ita ta hana wani kokwanto ya shiga zuciyarsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, kowaɗanne masu addini suna da inda suke fuskanta lokacin addininsu, ko dai da umarnin Allah suke yi ko kuma su ne suka ƙirƙirara wa kansu hakan ta hanyar bidi'a. Saboda haka sai ya umarci muminai da su riƙa yin takara da juna wajen aikin alheri, ya ƙarfafe su ta hanyar shaida musu cewa, duk inda suke mutuwa za ta riske su, kuma wajensa ne kaɗai makomarsu take gaba ɗaya ranar gobe ƙiyama, domin shi Allah babu abin da yake gagarar sa.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar Annabinsa (ﷺ) da ya mayar da Ka'aba alƙiblarsa a duk inda yake, domin wannan ita ce gaskiyar da babu sofanen shakka a cikinta, kuma Allah ba mai rafkana ba ne game da aikin bayinsa, yana sane da aikin kowa, kuma zai yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa. Har wa yau Allah ya sake nanata wa Annabinsa (ﷺ) umarnin ya fuskanci Ka'aba yayin sallarsa a duk inda yake, su ma muminai duk inda suke su fuskanci Ka'aba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo musu wannan canji ne don ya rushe hujjar Yahudawa da suke kafa wa Annabi (ﷺ) da Musulmai cewa, su daina sukan addininsu na Yahudanci, don ga shi su ma shi suke kwaikwaya, suna kallon alƙiblarsu idan suna ibada, kuma wai tun da har Musulmai sun yarda da alƙiblarsu, wannan ya nuna su ne a kan gaskiya, dole ne su zo su bi addininsu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rushe wannan hujjar tasu daga tushenta.
To yanzu babu wata hujja da ta rage, sai wata rarraunar hujja ta mushirikai masu cewa, tun da Annabi da sahabbai sun dawo suna fuskantar alƙiblarsu, to ya zama dole su zo su bi addininsu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da kada su yi shayin waɗannan azzalumai, ko su ji tsoron rarraunar hujjarsu, su dai su ji tsoron sa shi kaɗai, domin shi ne wanda ya cancanta a ji tsoro.
Daga nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara bayyana wata hikima ta samar da wannan canji na alƙibla, watau ya tabbatar wa muminai cewa, ya cika musu shari'o'in addininsu da kuma fatan su miƙa wuya ga umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) don su sami shiriyarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin gode wa Allah a kan ni'imominsa. Godiyar Allah tana kasancewa ne da zuciya, da harshe, da kuma gaɓoɓi.

2. Haramcin butulce wa ni'imar Allah.

3. Haƙuri da tsayar da salla suna taimaka wa rayuwar bawa ta yi kyau duniya da lahira.
4. Manzon Allah (ﷺ), kamar yadda ya koyar da ayoyin Alƙur'ani ga sahabbansa, hakanan ya koyar da su ma'anoninsa ta hanyar Sunnarsa. Don haka ba ta yiwuwa a raba tsakanin Alƙur'ani da Sunnar Annabi (ﷺ) wajen fahintar addinin Musulunci.

Suratul Baƙara (151-157)

كَمَآ أَرۡسَلۡنَا فِيكُمۡ رَسُولٗا مِّنكُمۡ يَتۡلُواْ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتِنَا وَيُزَكِّيكُمۡ وَيُعَلِّمُكُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَيُعَلِّمُكُم مَّا لَمۡ تَكُونُواْ
تَعۡلَمُونَ ١٥١ فَٱذۡكُرُونِيٓ أَذۡكُرۡكُمۡ وَٱشۡكُرُواْ لِي وَلَا تَكۡفُرُونِ ١٥٢ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱسۡتَعِينُواْ بِٱلصَّبۡرِ وَٱلصَّلَوٰةِۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٥٣
وَلَا تَقُولُواْ لِمَن يُقۡتَلُ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ أَمۡوَٰتُۢۚ بَلۡ أَحۡيَآءٞ وَلَٰكِن لَّا تَشۡعُرُونَ ١٥٤ وَلَنَبۡلُوَنَّكُم بِشَيۡءٖ مِّنَ ٱلۡخَوۡفِ وَٱلۡجُوعِ وَنَقۡصٖ مِّنَ
ٱلۡأَمۡوَٰلِ وَٱلۡأَنفُسِ وَٱلثَّمَرَٰتِۗ وَبَشِّرِ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٥٥ ٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَٰبَتۡهُم مُّصِيبَةٞ قَالُوٓاْ إِنَّا لِلَّهِ وَإِنَّآ إِلَيۡهِ رَٰجِعُونَ ١٥٦ أُوْلَٰٓئِكَ عَلَيۡهِمۡ صَلَوَٰتٞ
مِّن رَّبِّهِمۡ وَرَحۡمَةٞۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُهۡتَدُونَ ١٥٧

151. Kamar yadda Muka aiko muku da wani manzo daga cikinku, yana karanta muku ayoyinmu, kuma yana tsarkake ku, kuma yana koyar da ku Littafi da Hikima, kuma yana koyar da ku abin da a da can ba ku sani ba.

152. Don haka ku ambace Ni, Ni ma zan ambace ku, kuma ku gode Mini, kada kuma ku kafirce Mini.

153. Ya ku waɗanda suka yi imani ku nemi taimako ta hanyar haƙuri da salla. Lalle Allah Yana tare da masu haƙuri.

154. Kada kuma ku ce wa waɗanda ake kashewa a kan hanyar Allah su matattu ne. A'a, rayayyu ne, sai dai ku ne ba ku sani ba.

155. Kuma lalle za Mu jarrabe ku da wani abin tsoro da yunwa da tawayar dukiya da ta rayuka da ta 'ya'yan itatuwa. Don haka ka yi albirshir ga masu haƙuri.

156. (Su ne) waɗanda idan wata musiba ta same su sai su ce: “Lalle mu na Allah ne, kuma lalle mu gare Shi muke komawa.”

157. Waɗannan suna da yabo daga Ubangijinsu da rahma, kuma waɗannan su ne shiryayyu.

Bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci cewar, ɗaya daga cikin dalilan da suka sa ya canza wa muminai alƙiblarsu zuwa Ka’aba shi ne don ya cika musu ni’imarsa ta hanyar yi musu bayanin shari’un Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). To kamar irin haka ne ya yi musu wata ni’imar ta aiko da Annabi (ﷺ) a cikinsu, wanda sun san shi sarai, sun san nasabarsa da halayensa na ƙwarai, kuma ya aiko shi yana magana da harshensu na Larabci, yana karantar da su Alƙur’ani, yana yi musu kyakkyawar tarbiyya, ta hanyar koyar da su halaye na ƙwarai da hana su aikata laifuka da saɓon Allah. Ya karantar da su ma’anonin Alƙur’ani, tare da yaɗa sunnarsa a tsakaninsu, yana sanar da su abubuwa da yawa, waɗanda a da ba su san su ba, kamar labarun al’ummomin da suka gabata, da manzanninsu, da duk wani abu na ilimi wanda hankali kaɗai ba zai kai gare shi ba, sai ta hanyar wahayi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa da ambaton sa, ambato na zuciya da na harshe da na gaɓoɓi, idan sun yi hakan, shi ma zai ambace su. Annabi (ﷺ) a wani Hadisi ƙudusi ya ce, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: “Ni ina nan a duk inda zaton bawana yake gare ni, ni ina tare da shi; idan ya ambace ni a ransa, ni ma zan ambace shi a raina; idan ya ambace ni a cikin wani taro, ni ma zan ambace shi a cikin taron da ya fi nasa alheri.” [Bukhari #7405 da Muslim #2675]. Hakanan Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: “Babu wasu mutanen da za su taru a wani ɗaki daga ɗakunan Allah, suna karanta littafin Allah, suna darasin sa a tsakaninsu, face sai nutsuwa ta sauka a kansu, rahama ta lulluɓe su, mala’iku sun zagaye su, kuma Allah ya ambace su a wajen waɗanda suke tare da shi.” [Muslim #2699]. Kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su gode wa ni’imomin da ya yi musu masu yawa, kada su yi butulci.
Kasancewar bawa ba ya rabuwa da ɗaya daga cikin halaye guda biyu, ko dai yana cikin ni’ima, to sai ya yi wa Allah godiya, ko kuma yana cikin musiba, to sai ya yi haƙuri, don haka sai Allah ya kira muminai, ya umarce su da yin haƙuri da tsayar da salla. Domin haƙuri da tsayar da salla, suna taimaka wa bawa wajen fuskantar duk wasu matsaloli na rayuwar duniya, domin wanda duk ya siffantu da su, to yana tare da Allah, cikin taimakonsa da agajinsa.
Sannan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana muminai su kira ‘yan’uwansu da aka kashe wajen ɗaukaka kalmar Allah da sunan ‘matattu’; a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) su ba matattu ba ne, a’a, rayayyu ne, suna can cikin jin daɗi na Aljanna, duk da cewa mutane ba su fahinci haka ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa bayinsa muminai cewa, zai jarrabe su da ɗan wani abu kaɗan na tsoro da zai jefa a cikin zukatansu ko yunwa da za ta kama su ko na asarar dukiyoyi da rayuka ko na ƙarancin abinci, to sai Allah ya umarci Annabinsa (ﷺ) da ya yi wa masu haƙuri albishir. Su ne waɗanda idan wani bala’i ya same su, sai su ce: “Lalle mu na Allah ne, kuma lalle mu gare shi muke komawa.” Wato su bayin Allah ne masu miƙa wuya da sallamawa gare shi, kuma bayan mutuwarsu su tabbatar da wurinsa za su koma, inda zai saka wa kowa gwargwadon aikinsa. To waɗannan masu haƙuri suna da yabo da martaba sha’aninsu daga Allah, kuma rahamar Allah Ubangijinsu za ta lulluɓe su ta

ko’ina, kuma su ne waɗanda Allah ya yi musu gyaɗar dogo a nan duniya, suka dace da shiriyar Allah, suka bi ta.
An karƀo daga Ummu Salama (Allah ya kara mata yarda) ta ce: “Na ji Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Babu wani Musulmi da wata musiba za ta same shi, sai ya faɗi abin da Allah ya umarce shi, ya ce: ‘Lalle mu na Allah ne, kuma lalle mu zuwa gare shi muke komawa, Allah ka ba ni lada a kan musibar nan tawa, kuma ka musanya min ita da mafi alheri.’ face sai Allah ya musanya masa da wadda ta fi ta alheri.” [Muslim #918].

Suratul Baƙara (158)

۞ إِنَّ ٱلصَّفَا وَٱلۡمَرۡوَةَ مِن شَعَآئِرِ ٱللَّهِۖ فَمَنۡ حَجَّ ٱلۡبَيۡتَ أَوِ ٱعۡتَمَرَ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡهِ أَن يَطَّوَّفَ بِهِمَاۚ وَمَن تَطَوَّعَ خَيۡرٗا فَإِنَّ ٱللَّهَ شَاكِرٌ عَلِيمٌ ١٥٨

158. Lalle dutsen Safa da na Marwa suna cikin alamomin bautar Allah, don haka wanda ya je Hajji ga Ɗakin Allah ko ya je Umara, to babu wani laifi a gare shi ya yi ɗawafi tsakaninsu. Kuma wanda ya yi biyayya ta hanyar aikata alheri, to lalle Allah Mai godiya ne kuma Masani.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana a kan sa’ayi tsakanin Safa da Marwa. Safa da Marwa wasu duwatsu ne guda biyu a cikin garin Makka. Lokacin da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ajiye kuyangarsa Hajara a kwazazzabon Makka, ita da jaririnta Isma’il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), yayin da ruwansu na sha ya ƙare, Hajara ta ga ɗanta Isma’il yana ta kukan ƙishirwa, ga shi kuma ba ta da abin da za ta ba shi, sai ta tashi ta je ta hau kan dutsen Safa, ko za ta tsinkayo wani wanda zai taimake ta da ruwan sha, ba ta ga kowa ba. Ta gangaro ta nufi Marwa, nan ma ta hau, ba ta tsinkayo kowa ba. Ta yi haka har sau bakwai. Wannan shi ne dalilin yin sa’ayi guda bakwai a tsakaninsu yayin gudanar da aikin haji ko umara.
A lokacin jahiliyya bayan Abdulmuttalib, kakan Annabi (ﷺ), ya sake haƙan rijiyar Zamzam bayan ƙafewarta, sai ya ɗauke wasu gumaka guda biyu waɗanda aka ajiye kusa da ita, ɗaya ana kiran sa Isaf, ɗayan kuma Na’ila; sai ya mayar da Isaf kan dutsen Safa, ya ɗora Na’ila a kan dutsen Marwa. Daga nan sai wasu ƙabilun Larabawa in sun zo Hajji a lokacin jahiliyya, sai su riƙa yin sa’ayi a tsakanin waɗannan duwatsu guda biyu, saboda gumakan da aka ɗora a kansu. To bayan zuwan Musulunci da aka shar’anta Hajji da umara, sai wasu daga cikin Musulmi suka riƙa jin nauyin ci gaba da yin sa’ayi a tsakanin waɗannan duwatsu guda biyu, sai Allah ya saukar da wannan ayar, yana faɗa musu cewa, su ma waɗannan duwatsu suna daga cikin alamomin bautar Allah, kuma masu dangantaka da tarihin Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ɗansa Annabi Isma’il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), don haka babu wani laifi don sun yi sa’ayi a duwatsun. Kuma duk wanda ya aikata farilla, sannan ya ƙara da taɗawwu’i, to shi ma Allah zai ƙara masa a ladansa domin Allah mai godiya ne, ba ya lalata aikin mutum na ƙwarai, kuma masani ne da yake sane da aikin bawansa na alheri, kuma zai ga sakamakonsa.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɓoye gaskiya bayan saninta babban laifi ne da yake jawo wa mai yin sa la’anar Allah, da ta mala’iku, da ta sauran halittun Allah.

2. Suka ga malaman da suke ɓoye wa mabiyansu gaskiya don ta saba wa ayyukansu ko ta hanyar yin shiru su ƙi cewa komai a kai ko kuma ta hanyar su umarce su da kishiyar wannan gaskiya. Duk wani malami mai kira zuwa ga abin da yake yaɗa bidi’a ne a addini ko ya san saɓon Allah ne, to ya shiga ƙarƙashin wannan ayar.

3. Kofar tuba a buɗe take ga duk wani mai son ya tuba, don haka kada wani mai laifi ya ɗebe ƙauna daga samun rahamar Allah. Sharaɗin ingancin tubansa shi ne, ya janye daga laifin da yake kai, ya kyautata aikinsa, ya bayyana abin da ya kasance yana ɓoyewa na gaskiya, to idan har ya aikata hakan, ya sa ran samun rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Duk da kasancewar la'antar Allah kaɗai ga bawa ta isa ta haramta masa samun rahama duniya da lahira, to amma sai Allah ya haɗa masa da la'antar mala'iku da ta mutane gaba ɗaya, domin a fahinci cewa, babu wani wanda zai tausaya masa, har ya nema masa ceto a wurin Allah, a'a, kowa fushi yake da shi, yana kira masa la'antar Ubangiji.

Suratul Baƙara (159-162)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡتُمُونَ مَآ أَنزَلۡنَا مِنَ ٱلۡبَيِّنَٰتِ وَٱلۡهُدَىٰ مِنۢ بَعۡدِ مَا بَيَّنَّٰهُ لِلنَّاسِ فِي ٱلۡكِتَٰبِ أُوْلَٰٓئِكَ يَلۡعَنُهُمُ ٱللَّهُ وَيَلۡعَنُهُمُ ٱللَّٰعِنُونَ ١٥٩ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُواْ وَأَصۡلَحُواْ وَبَيَّنُواْ فَأُوْلَٰٓئِكَ أَتُوبُ عَلَيۡهِمۡ وَأَنَا ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ١٦٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَمَاتُواْ وَهُمۡ كُفَّارٌ أُوْلَٰٓئِكَ عَلَيۡهِمۡ لَعۡنَةُ ٱللَّهِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلنَّاسِ أَجۡمَعِينَ ١٦١ خَٰلِدِينَ فِيهَا لَا يُخَفَّفُ عَنۡهُمُ ٱلۡعَذَابُ وَلَا هُمۡ يُنظَرُونَ ١٦٢

159. Lalle waɗanda suke ɓoye abin da Muka saukar na hujjoji da shiriya bayan Mun yi bayanin su ga mutane a cikin Littafi, to waɗannan su ne Allah Yake la'antar su, kuma masu la'anta su ma suke la'antar su.

160. Sai dai waɗanda suka tuba kuma suka gyara kuma suka bayyana, to waɗannan zan karɓi tubansu, kuma lalle Ni Mai karɓar tuba ne, Mai jin ƙai.

161. Lalle waɗanda suka kafirta kuma suka mutu suna kafirai, to waɗannan la'anar Allah ta tabbata a kansu da ta mala'iku da mutane gaba ɗaya.

162. Suna masu dawwama a cikinta, ba za a sassauta masu azaba ba kuma ba za a saurara musu ba.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba ne da sukan malaman Yahudawa da Nasara, saboda suna ɓoye wa mutane abin da yake cikin Attaura da Linjila, na hujjoji bayyanannu game da gaskiyar annabcin Annabi (ﷺ). Wannan sukar ta haɗa da duk wani wanda yake aikata irin aikinsu na ɓoye gaskiya bayan ya san ta. Allah ya bayyana sakamakon masu irin wannan mummunar ɗabi'a da cewa, za su haɗu da la'anar Allah da ta mala'iku da ta muminai ko duk wata halitta ta Ubangiji. Babu mai kuɓuta daga wannan la'antar sai wanda ya tuba ya gyara laifinsa, ta hanyar bayyana wa mutane abin da ya ɓoye masu na gaskiya, to waɗannan su ne Allah zai karɓi tubansu, ya yafe musu laifinsu, saboda shi mai karɓar tuba ne, mai rahama ga bayinsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka kafirce masa, suka watsar da addinin da ya saukar na Musulunci, suka rayu a kan kafirci har mutuwa ta zo musu, Allah ya bayyana cewa, za su ci gaba da dawwama a cikin la'antar Allah da mala'iku da halittu gaba ɗaya, za kuma su zarce zuwa wutar Jahannanma a lahira, inda za su dawwama a cikinta har abada kuma babu ranar da za a sassauta musu azaba, ko a ɗan jinkirta musu ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda zai yi duba na tsanaki cikin halittun da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ajiye a sararin samaniya da bayan ƙasa, zai ƙara samun sakankancewa da girman sha'anin Allah, zai ƙara samun haɓakar imani a zuciyarsa.

2. Duk wanda ya daidaita son wanin Allah da son Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a zuciyarsa, to ya yi wa Allah shirka, ya mayar da wannan abu kishiya ga Allah.

3. Duk sa'adda imanin bawa ya ƙaru, to soyayyarsa ga Allah ita ma za ta ƙaru.

4. Duk wata soyayya a duniya da ba a gina ta a kan shari'a ba, to a lahira za ta rikiɗe ta koma matsananciyar gaba, kamar yadda ya zo a cikin *Suratu Maryam*, aya ta 81-82 da *Suratul Ankabut*, aya ta 25 da *Suratu Saba'i, aya* ta 31-33.

Suratul Baƙara (163-167)

وَإِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ ۖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلرَّحْمَٰنُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٦٣﴾ إِنَّ فِى خَلْقِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَٱخْتِلَٰفِ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَٱلْفُلْكِ ٱلَّتِى تَجْرِى فِى ٱلْبَحْرِ بِمَا يَنفَعُ ٱلنَّاسَ وَمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مِن مَّآءٍ فَأَحْيَا بِهِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا وَبَثَّ فِيهَا مِن كُلِّ دَآبَّةٍ وَتَصْرِيفِ ٱلرِّيَٰحِ وَٱلسَّحَابِ ٱلْمُسَخَّرِ بَيْنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿١٦٤﴾ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَندَادًا يُحِبُّونَهُمْ كَحُبِّ ٱللَّهِ ۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَشَدُّ حُبًّا لِّلَّهِ ۗ وَلَوْ يَرَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓا۟ إِذْ يَرَوْنَ ٱلْعَذَابَ أَنَّ ٱلْقُوَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًا وَأَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعَذَابِ ﴿١٦٥﴾ إِذْ تَبَرَّأَ ٱلَّذِينَ ٱتُّبِعُوا۟ مِنَ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوا۟ وَرَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ وَتَقَطَّعَتْ بِهِمُ ٱلْأَسْبَابُ ﴿١٦٦﴾ وَقَالَ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوا۟ لَوْ أَنَّ لَنَا كَرَّةً فَنَتَبَرَّأَ مِنْهُمْ كَمَا تَبَرَّءُوا۟ مِنَّا ۗ كَذَٰلِكَ يُرِيهِمُ ٱللَّهُ أَعْمَٰلَهُمْ حَسَرَٰتٍ عَلَيْهِمْ ۖ وَمَا هُم بِخَٰرِجِينَ مِنَ ٱلنَّارِ ﴿١٦٧﴾

163. Kuma abin bautarku abin bauta ne Guda Ɗaya, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Shi ne Mai rahma, Mai jin ƙai.

164. Lalle a cikin halittar sammai da ƙasa da sassaɓawar dare da rana da jiragen ruwa da suke tafiya a kan ruwa da abin da yake amfanar mutane da kuma abin da Allah Ya saukar daga sama na ruwa, Ya rayar da ƙasa da shi bayan mutuwarta, Ya kuma yaɗa duk wata halitta mai tafiya a cikin (ƙasa) da jujjuyawar iska, da kuma girgije da aka hore shi tsakanin sama da ƙasa, lalle akwai ayoyi ga mutane masu hankali.

165. Kuma akwai wasu mutane waɗanda suke bauta wa wasu kishiyoyi ba Allah ba; suna son su kamar son Allah; waɗanda kuwa suka yi imani sun fi son Allah (fiye da komai). Da a ce waɗanda suka yi zalunci za su ga lokacin da suke ido huɗu da azaba (to da sun gane) cewa, lalle duk wani ƙarfi na Allah ne gaba ɗaya, kuma lalle Allah Mai tsananin azaba ne.

166. Lokacin da waɗanda aka yi wa biyayya (shugabanni) za su nisantar da kansu daga waɗanda suka yi musu biyayya (mabiya), kuma suka yi arba da azaba, kuma duk wasu alaƙoƙi da ke tsakaninsu suka yanke.

167. Kuma waɗanda suka yi biyayya suka ce: "Ina ma dai muna da wata dama ta komawa (duniya) don mu ma mu nisantar da kanmu daga gare su, kamar yadda suka nisanta kansu daga gare mu?" Kamar

haka ne Allah Yake nuna musu ayyukansu suka zama nadama a gare su, kuma su ba masu samun fita ne daga wuta ba.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da bayinsa cancantarsa su bauta masa shi kaɗai, ba tare da sun haɗa shi da komai ba, domin shi ne ya siffantu da siffofi na kamala, kamar yalwatacciyar rahamarsa ga kowa da komai da kuma keɓantacciyar rahamarsa ga muminai ranar gobe ƙiyama. Sannan ya lissafa musu kaɗan daga cikin manyan ayyukansa na Rububiyya, waɗanda suka ƙunshi ni'imomi masu girma ga halittunsa, waɗanda ko su kaɗai aka duba sun isa zama babbar hujja a kan cancantarsa da bauta shi kaɗai. Waɗannan ni'imomi da Allah ya ambata a nan, sun haɗa da halittar sammai da ƙasa da irin abubuwan mamaki masu girma da ya ajiye a cikinsu; da zuwan dare da rana a kullum cikin tsari guda ɗaya, ba tare da sun yanke ba, suna sauka da haske da duhu da zafi da sanyi da tsawo da gajarta; da kuma manyan jiragen ruwa masu keta teku daga ƙasa zuwa ƙasa danƙare maƙil da kayan amfanin mutane; da kuma ruwan sama da yake saukarwa, ya fitar da tsirrai da shi, ya raya ƙasa bayan ta bushe, sannan ya yaɗa dabbobi iri-iri a bayan ƙasa. Sannan yake sako iska daban-daban, wata mai kaɗawa da ƙarfi, wata a hankali, wata mai zafi, wata kuma mai sanyi, wata mai amfani, wata kuma mai cutarwa. Hakannan kuma yadda yake hore haɗuwar girgije tsakanin sama da ƙasa don masalahar bayinsa.
Duk waɗannan ayyuka ya yi su ne domin su nuna wa bayinsa cikar Kudirarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai, da a ce mutane za su yi aiki da hankulan da ya ba su. To amma duk da irin waɗannan dalilai na zahiri, sai ga wasu mutane suna ɗaukan wasu halittu su daidaita su da Allah wajen bauta da soyayya, suna son su kamar yadda suke son Allah. Amma Allah ya tabbatar da cewa, waɗanda suka yi imani su ne suke son Allah fiye da yadda waɗannan mutane suke son kishiyoyin da suka yi wa Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya juyo da magana zuwa ga Annabi (ﷺ) cewa, ina ma da ya ga halin da waɗannan mutanen masu fifita son wanin Allah a kan son Allah, za su tsinci kansu a ciki, su ma ina ma a ce sun ga hakan, lokacin da za su yi ido huɗu da azabar Allah ranar alƙiyama, daga lokacin ne za su tabbatar da cewa, duk wani ƙarfi da wani iko na Allah ne shi kaɗai, kuma irin azabar da ya yi tanadi ga masu kafirce masa ko yin shirka da shi mai tsanani ce.
A ranar kuma duk wasu shugabanni na ɓata za su nisantar da kansu daga mabiyansu, su ma mabiyan za su yi haka, domin dukkansu sun ga azabar Allah ƙuru-ƙuru, duk wata dangantaka tsakaninsu a rananr ta ƙare, babu sauran ƙauna da za ta wanzu a lokacin. A lokacin ne mabiya za su yi burin ina ma za su samu wata dama ta komawa duniya don su yi baram-baram da waɗannan shugabannin nasu na ɓata, kamar yadda suka yi musu a lahira bayan sun nuna musu matuƙar ƙauna da soyayya da ta kai matakin bauta a gare su ba Allah ba. Sai dai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya gama nuna musu taɓewar ayyukansu, kamar yadda ya nuna musu azaba, domin su cika da nadama da yin da-na-sani marar amfani, domin wuta ce makomarsu ta har abada, babu ranar fita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramta abin da Allah bai haramta ba, ko halatta abin da Allah ya haramta biyyaya ce ga Shaiɗan, kuma yi wa Allah ƙarya ne.

2. Duk wanda ya kauce wa gaskiya da abin da Allah ya saukar, to wannan mutum ne marar hankali, kuma ba shiryayye ba.

3. Arziki na Allah ne, don haka a wurinsa kawai ya wajaba mutum ya nema.

4. Yana daga cikin bautar mutum ga Allah, ya gode wa ni'imominsa.

5. Allah ne kaɗai mai haƙƙin ya haramta ko ya halatta.

Suratul Baƙara (168-173)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ كُلُواْ مِمَّا فِى ٱلْأَرْضِ حَلَـٰلًا طَيِّبًا وَلَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيْطَـٰنِ ۚ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوٌّ مُّبِينٌ ﴿١٦٨﴾ إِنَّمَا يَأْمُرُكُم بِٱلسُّوٓءِ وَٱلْفَحْشَآءِ
وَأَن تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿١٦٩﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱتَّبِعُواْ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُواْ بَلْ نَتَّبِعُ مَآ أَلْفَيْنَا عَلَيْهِ ءَابَآءَنَآ ۚ أَوَلَوْ كَانَ ءَابَآؤُهُمْ لَا
يَعْقِلُونَ شَيْـًٔا وَلَا يَهْتَدُونَ ﴿١٧٠﴾ وَمَثَلُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ كَمَثَلِ ٱلَّذِى يَنْعِقُ بِمَا لَا يَسْمَعُ إِلَّا دُعَآءً وَنِدَآءً ۚ صُمٌّۢ بُكْمٌ عُمْىٌ فَهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿١٧١﴾
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُلُواْ مِن طَيِّبَـٰتِ مَا رَزَقْنَـٰكُمْ وَٱشْكُرُواْ لِلَّهِ إِن كُنتُمْ إِيَّاهُ تَعْبُدُونَ ﴿١٧٢﴾ إِنَّمَا حَرَّمَ عَلَيْكُمُ ٱلْمَيْتَةَ وَٱلدَّمَ وَلَحْمَ
ٱلْخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ بِهِۦ لِغَيْرِ ٱللَّهِ ۖ فَمَنِ ٱضْطُرَّ غَيْرَ بَاغٍ وَلَا عَادٍ فَلَآ إِثْمَ عَلَيْهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٧٣﴾

168. Ya ku mutane, ku ci halal mai daɗi na abin da ke fitowa daga cikin ƙasa, kada kuma ku bi hanyoyin Shaiɗan, lalle shi maƙiyi ne mai bayyana ƙiyayya a gare ku.

169. Yana umartar ku ne kawai da saɓo da ayyakan assha da kuma faɗin abin da ba ku da ilimi game da shi ku jingina wa Allah.

170. Idan kuma aka ce musu: “Ku bi abin da Allah Ya saukar”, sai su ce: “A'a, za dai mu bi abin da muka samu iyayenmu a kansa”. To, ko da iyayensu ba sa hankaltar komai, kuma ba sa shiryuwa?

171. Misalin waɗanda suka kafirta kamar misalin wanda yake ɗaga sauti ne ga wanda ba ya jin (komai) sai kira da sowa. Kurame ne, bebaye ne, makafi ne, don haka su ba sa hankalta.

172. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ci daga daɗaɗan abin da Muka arzuta ku (da shi), kuma ku yi godiya ga Allah in har kun kasance Shi kaɗai kuke bauta wa.

173. (Allah) Ya haramta muku mushe ne kawai da jini da naman alade da abin da aka kira sunan wani ba Allah ba (lokacin yanka shi). Don haka duk wanda ya matsu, ba mai zalunci ba, kuma ba mai ƙetare iyaka ba, to babu laifi a kansa ya ci. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana kiran mutane gaba ɗaya, muminansu da kafiransu da cewa, su ci abin da ya arzuta su da shi na dabbobi da tsirrai da kayan marmari, matuƙar abin da za su ci ya cika sharuɗɗa guda biyu, wato ya zamanto abin da Allah ya halatta amfani da shi ne, sannan kuma ba mai cutarwa ne ba. Sannan ya ɦana su biyayya ga Shaiɗan wajen haramta abin da Allah ya halatta ko halatta abin da ya haramta, domin Shaiɗan babban maƙiyinsu ne, mai nuna adawarsa gare su a fili, ba zai taɓa son su da wani alheri ba, sai dai ya riƙa yi musu ingiza-mai-kantu-ruwa, ya sa su aikata munanan ayyuka da miyagun ɗabi’u, waɗanda suka kai matuƙa a muni; ba ma iya nan kaɗai zai tsaya ba, a’a, sai ya riƙa sa su suna yi wa Allah ƙarya, suna ƙirƙirar wasu dokoki na banza suna cewa daga Allah suke, watau dai su haramta, su kuma halatta, bisa son zuciya, ba da wani dalili ba.Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cewa, mushirikai sun kasance duk sa’adda aka nemi su zo su bi abin da ya zo daga Allah, su amince duk abin da za su halatta ko su haramta, ya tafi daidai da shari’ar Allah, sai ka samu amsarsu ɗaya ce, ba za su taɓa sakin abin da suka tashi suka gada daga iyaye da kakanni ba. Allah ya soki irin wannan makauniyar biyayyar da suke yi wa iyayensu, kuma a kan me za su riƙa koyi da waɗanda bai cancanta su yi koyi da su ba, saboda ba su yi aiki da hankalinsu ba wajen bin gaskiya, kuma ba su da wani ilimi wanda yake musu jagoranci a cikin rayuwarsu ta addini da ta duniya?

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin kafirai, waɗanda idan mai wa'azi ya zo musu, yana faɗa musu gaskiya, sam ba sa fahimtar komai daga abin da yake faɗa, ko da kuwa sun saurare shi. Misalinsu kamar makiyayi ne a tsakiyar dabbobinsa da yake ƙwala kira, suna dai jin sautinsa, amma ba sa gane ma'anar maganarsa, to hakanan waɗannan kafiran suke. Lokacin da suka bijire wa imani da Annabi (ﷺ) a karon farko, sai kafofin jinsu da ganinsu da fahintarsu duk suka doɗe, ba sa jin gaskiya su fahince ta, balle su karɓa, ba sa iya faɗar gaskiya, ba sa kuma ganin hanyar gaskiya balle su bi ta, a dalilin haka ba sa fahintar wani abu na gaskiya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su ci abin da yake tsattsarka ne, mai amfani, wanda Allah ya arzuta su da shi, kuma su tsaya su gode masa a kan ire-iren waɗannan ni'imomi da ya yi musu, godiya da zuciyoyinsu da harsunansu da gaɓoɓins. To idan har sun kasance masu biyayya ne da miƙa wuya da ƙanƙantar da kansu ga Allah, to za su yi aiki da wannan umarni da yake yi musu.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa da cin halal mai daɗi, sai kuma ya lissafa musu wasu abubuwan da aka haramta musu ci. Allah ya haramta musu cin mushen dabbar da ta mutu, ba tare da an yanka ta ba yanka na shari'a da jinin da ya kwararo daga wata dabba da naman alade da abin da aka yanka shi da sunan wanin Allah, kamar dabbar da ake yanka wa gumaka da makamancinta. To amma a nan an yi togaciyar lokacin larura, mutum yana iya cin wani abu daga waɗannan da aka ambata gwargwadon lalurarsa, to duk wanda ya yi haka to ba shi da wani laifi, Allah mai gafara ne tun da ya ɗauke masa zunubi, mai rahama ne yayin da ya yalwata wa bayinsa, bai takura musu ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramun ne mutumin da Allah ya ba shi ilimi ya ɓoye shi, ya ƙi sanar da kowa, musamman lokacin da al'umma take buƙatar iliminsa.

2. Tabbatar wa da Allah sifar mamaki, kamar yadda ta dace da Zantinsa, Maɗaukakin Sarki.

3. Gwargwadon laifin mutum, gwargwadon jinsin sakamakonsa. Wannan shi yake tabbatar da cikar adalci na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Baƙara (174-176)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡتُمُونَ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَيَشۡتَرُونَ بِهِۦ ثَمَنٗا قَلِيلًا أُوْلَٰٓئِكَ مَا يَأۡكُلُونَ فِي بُطُونِهِمۡ إِلَّا ٱلنَّارَ وَلَا يُكَلِّمُهُمُ ٱللَّهُ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَلَا يُزَكِّيهِمۡ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٌ ١٧٤ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱشۡتَرَوُاْ ٱلضَّلَٰلَةَ بِٱلۡهُدَىٰ وَٱلۡعَذَابَ بِٱلۡمَغۡفِرَةِۚ فَمَآ أَصۡبَرَهُمۡ عَلَى ٱلنَّارِ ١٧٥ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ نَزَّلَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّۗ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ ٱخۡتَلَفُواْ فِي ٱلۡكِتَٰبِ لَفِي شِقَاقِۭ بَعِيدٖ ١٧٦

174. Lalle waɗanda suke ɓoye abin da Allah Ya saukar na Littafi, kuma suke musanya shi da ɗan kuɗi kaɗan, waɗannan babu abin da suke ci a cikkunansu sai wuta, kuma Allah ba zai yi musu magana ba ranar tashin alƙiyama, kuma ba zai tsarkake su ba, kuma lalle suna da wata azaba mai raɗaɗi.

175. Waɗannan su ne waɗanda suka zaɓi ɓata a madadin shiriya da kuma azaba a madadin gafara. Don haka yi mamakin haƙurin (zamansu) a cikin wuta.

176. Wannan ya faru ne saboda lalle Allah Ya saukar da Littafinsa da gaskiya. Kuma lalle duk waɗanda suka yi saɓani dangane da Littafin, tabbas suna cikin saɓawa mai nisa.

Bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin cewa ya halatta duk wani abu mai daɗi da amfani ga mutane, ya kuma wajabta musu gode wa ni'imominsa, sai kuma ya kawo bayani a kan miyagun

malamai masu ɓoye gaskiya, suna shar’anta wa mabiyansu shari’o’i waɗanda ba na Allah ba, kamar malaman Yahudawa da Nasara, waɗanda suka ɓoye gaskiyar annabcin Annabi (ﷺ) bayan sun karanta siffofinsa a Attaura da Linjila, suka riƙa wasa da hukunce-hukuncen Allah, su sassauta wasu, su canza wasu, domin kwaɗayin abin duniya ko samun matsayi, ba su san cewa, dukiyar da suke ci sakamakon canza hukuncin Allah, wuta ce suke ci a cikinsu, kuma ranar gamuwarsu da Allah, ba za su ji wata magana mai daɗi daga gare shi ba, ba zai tsarkake su daga zunubbansu ba; a madadin haka sai dai su haɗu da azaba mai raɗaɗin gaske.
Waɗannan mutane masu ɓoye ilimi da irin aikinsu na canza hanyar shiriya da wata ɓatacciyar hanya, suna barin gafarar Allah ne, su ɗauki azabarsa. Allah ya nuna mamakinsa game da wannan ƙarfin hali nasu na aikata aikin da zai kai su ga faɗawa wutar Jahannama, yaya suka iya yin haƙuri a kan aikin da zai kai su ga shiga azaba mai tsanani?! Waɗannan miyagun malamai lalle sun cancanci azabar Allah saboda ɓoye gaskiya da suka riƙa yi. Domin Allah dai ya saukar da Littafinsa da gaskiya kuma ya bayyana ta a fili a cikinsa, ashe bai dace a ɓoye ta ba, domin ɓoye ta ya saba da manufar Allah wajen saukar da littafinsa. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda suka ba da gaskiya da wani sashe na littafi, sannan suka kafirce wa wani sashi, suka ɓoye wani ɓangare na hukunce-hukuncensa, suka bayyana wani ɓangaren, to masu irin wannan ɗanyen aiki sun kauce wa hanyar gaskiya, sun yi nisa a cikin ɓata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Fuskantar gabas ko yamma don bauta ba shi ne kaɗai abin buƙata ga bawa ba; abin buƙata shi ne zuciyarsa ta cika da imani, sannan ya rungumi ayyukan alheri da kyautatawa.

2. La’akari da kusanci da tsananin buƙata yayin bayar da taimako ga mabuƙata kamar yadda Allah ya jero su a aya ta 177 sai dai idan an lura wani cikinsu ya fi buƙata, sai a gabatar da shi.

3. Girman sha’anin haƙuri da masu haƙuri.

4. Bayanin siffofin masu tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Babu masu aiki da dokokin Ubangiji sai masu imani, shi ya sa Allah ya kirawo muminai da sifarsu ta imani yayin gabatar musu da wannan doka.

Suratul Baƙara (177)
* لَّيْسَ ٱلْبِرَّ أَن تُوَلُّوا۟ وُجُوهَكُمْ قِبَلَ ٱلْمَشْرِقِ وَٱلْمَغْرِبِ وَلَٰكِنَّ ٱلْبِرَّ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلْكِتَٰبِ وَٱلنَّبِيِّۦنَ وَءَاتَى ٱلْمَالَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ ذَوِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينَ وَٱبْنَ ٱلسَّبِيلِ وَٱلسَّآئِلِينَ وَفِى ٱلرِّقَابِ وَأَقَامَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَى ٱلزَّكَوٰةَ وَٱلْمُوفُونَ بِعَهْدِهِمْ إِذَا عَٰهَدُوا۟ ۖ وَٱلصَّٰبِرِينَ فِى ٱلْبَأْسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَحِينَ ٱلْبَأْسِ ۗ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ صَدَقُوا۟ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ ﴿١٧٧﴾

177. Ba wai aikin ɗa'a shi ne ku juyar da fuskokinku mahudar rana ko mafaɗarta ba ; sai dai aikin ɗa'a shi ne, wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira da mala'iku da littattafai da annabawa, kuma ya bayar da dukiyarsa, alhalin yana son ta, ga dangi na kusa da marayu da mabuƙata da matafiyi da kuma masu roƙo (bisa larura) da 'yantar da bayi, sannan kuma ya tsayar da salla, kuma ya bayar da zakka, da kuma masu cika alƙawarinsu idan suka ƙulla alƙawari ; da masu haƙuri a cikin halin talauci da halin rashin lafiya da lokacin yaƙi. Waɗannan su ne waɗanda suka yi gaskiya, kuma waɗannan su ne masu taƙawa.

Bayan canza Alƙibla daga Baitul Maƙdis zuwa fuskantar Ka’aba, sai kuma rigima ta ci gaba tsakanin

Musulmi da abokan hamayyarsu Yahudawa, lokacin da su suke ganin sallar Musulmi babu ɗa'a ga Allah a cikinta, saboda sun daina fuskantar Baitul Maƙadis, alƙiblar annabawa. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa, tsayawa a dubi wata nahiya gabas ko yamma lokacin yin ibada, ba shi ne kawai ɗa'a ga Allah ba, ballantana har Yahudawa su riƙa ganin Musulmi ba sa yin ɗa'a ga Ubangiji, don sun daina fuskantar alƙiblarsu. Ɗa'a ta gaskiya ga Allah ita ce yin imani da Allah da ranar lahira da mala'iku da dukkan littattafan da Allah ya saukar wa annabawa da yin imani da dukkan annabawa da manzannin Allah, da kuma ba da kyautar dukiyarsa don Allah, tare da yana son abinsa, ya ba wa danginsa na kusa ko marayu ko mabuƙata ko matafiyin da guzurinsa ya yanke masa, ya taimaka masa da abin da zai mayar da shi garinsa da mai roƙo bisa larura, ko ya bayar da dukiyarsa don 'yanta bayi da makamantansu.
Hakanan kuma tsayar da salla kamar yadda ya kamata, da bayar da zakka ga masu ita, da cika alƙawari tsakanin bawa da Ubangijinsa ko tsakaninsa da 'yan'uwansa duk suna cikin ayyukan ɗa'a. Haƙuri ma a lokacin talauci ko rashin lafiya ko lokacin yaƙi duka ayyuka ne na ɗa'a. Wato mutum ya danne damuwarsa, ba tare da raki ba. To duk wanda ya siffantu da waɗannan siffofi da aka ambata, shi ne mai taƙawa, ta hanyar aikata wajibi, da barin abin da aka hana aikatawa.

Suratul Baƙara (178-179)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُتِبَ عَلَيۡكُمُ ٱلۡقِصَاصُ فِي ٱلۡقَتۡلَىۖ ٱلۡحُرُّ بِٱلۡحُرِّ وَٱلۡعَبۡدُ بِٱلۡعَبۡدِ وَٱلۡأُنثَىٰ بِٱلۡأُنثَىٰۚ فَمَنۡ عُفِيَ لَهُۥ مِنۡ أَخِيهِ شَيۡءٞ فَٱتِّبَاعُۢ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَأَدَآءٌ إِلَيۡهِ بِإِحۡسَٰنٖۗ ذَٰلِكَ تَخۡفِيفٞ مِّن رَّبِّكُمۡ وَرَحۡمَةٞۗ فَمَنِ ٱعۡتَدَىٰ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَلَهُۥ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١٧٨ وَلَكُمۡ فِي ٱلۡقِصَاصِ حَيَوٰةٞ يَـٰٓأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ١٧٩

178. Ya ku waɗanda suka yi imani, an wajabta muku *kisasi* dangane da waɗanda aka kashe; ɗa da ɗa, bawa da bawa, mace da mace. To duk wanda aka yafe masa ƙisasin ɗan uwansa, to sai ya bibiye shi ta hanyar da ta dace, shi kuma ya biya diyyar ta hanyar kyautatawa. Wannan (abin da aka ambata), sauƙi ne da rahama daga wajen Ubangijinku. Don haka duk wanda ya ƙetare iyaka bayan haka, to yana da azaba mai raɗaɗi.

179. Kuma a cikin (hukuncin) *kisasi* akwai (tsare) rayuwa a gare ku, ya ku ma'abota hankula, don ku samu taƙawa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai hukuncin zartar da ƙisasi a kan wanda ya yi kisan ganganci, kuma ya yi umarni da daidaito wajen wannan ƙisasi, wato a kashe ɗa yayin da ya kashe ɗa. Haka hukuncin yake yayin da namiji ɗa ya kashe 'ya mace ko bawa ya kashe bawa irinsa ko mace ta kashe mace irinta. Amma idan magadan wanda aka kashe suka yafe wa wanda ya yi kisan, to shi ke nan babu zancen ƙisasi, sai a bayar da diyya. To a irin wannan yanayi wajibi ne a kan shi wanda ya yi afuwa, kada ya riƙa goranta wa wanda ya yi wa afuwar ko ya riƙa jifan sa da wata baƙar magana, kuma kada ya ɗora masa nauyin da Allah bai ɗora masa ba. Shi kuma wanda aka yafe wa ya yi ƙoƙari ya biya diyyar da take kansa, ba tare da taurin bashi ba ko mummunar magana ga wanda ya yi yafiyar ba.
Cikin irin waɗannan hukunce-hukuncen da Allah ya saukar na ƙisasi, da yin afuwa da biyan diyya, akwai sauƙaƙawar gaske ga bayinsa, da rahama da tausayi gare su. To amma duk wanda ya yi wani ta'addanci daga baya, kamar ɗan'uwan mamaci ya kashe wanda aka yi wa afuwa, ko shi wanda aka yi wa afuwa, ya sake maimaita laifin kisan kai, to babu shakka wanda duk ya yi haka yana da wata azaba mai raɗaɗin gaske.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci hikimar shar'anta yin ƙisasi da cewa, shi ne kare rayuwar al'umma. Domin duk wanda ya san irin wannan hukunci na ƙisasi yana jiran sa idan har ya yi sanadiyyar

salwanta rayuwar ɗan'uwansa da ganganci, to babu shakka zai yi ƙoƙarin bijire wa zuciyarsa kan abin da za ta saƙa masa na aikin ta'addanci. Don haka wannan zai taimaka wajen rage yawan kashe-kashe ciki al'umma. Babu masu fahimtar irin wannan hikimar, sai masu hankula, waɗanda za su yi tunani da hankulansu domin fahintar hikimomin shari'a. Ba za a taba samun zaman lafiya ba, sai a ƙarƙashin bin dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wasiyya a zamanin jahiliyya wani sanannen abu ne a cikin al'ummar Larabawa. Sau tari sukan hana makusanci gado domin suna zargin cewa da man yana da sha'awar ganin ɗan'uwansa ya mutu don ya gaje shi, to sai su hana shi gadon ma gaba ɗaya. Hakanan babban ɗa namiji yakan kankane dukiyar mahaifinsa ya hana sauran 'yan'uwansa komai. To sai aka shar'anta wa mamaci idan ya zo mutuwa ya yi wasiyya a ba wa iyayensa da danginsa wani abu daga cikin dukiyarsa bayan ya mutu.

2. Muhimmanci sadar da zumunci. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta wasiyya ga iyaye da 'yan'uwa, saboda a kawar da abin da al'adar jahiliyya ta gadar musu na fifita wasu dangi a kan wasu, abin da sau da dama yakan sabbaba ƙiyayya da yanke zumunci a tsakanin dangi guda.

3. Rashin halaccin zartar da duk wata wasiyya da ta kauce wa tsarin shari'a da adalci, dole ne a yi mata gyara kafin a zartar da ita.

Suratul Baƙara (180-182

كُتِبَ عَلَيْكُمْ إِذَا حَضَرَ أَحَدَكُمُ ٱلْمَوْتُ إِن تَرَكَ خَيْرًا ٱلْوَصِيَّةُ لِلْوَٰلِدَيْنِ وَٱلْأَقْرَبِينَ بِٱلْمَعْرُوفِ ۖ حَقًّا عَلَى ٱلْمُتَّقِينَ ﴿١٨٠﴾ فَمَنۢ بَدَّلَهُۥ بَعْدَ مَا سَمِعَهُۥ فَإِنَّمَآ إِثْمُهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ يُبَدِّلُونَهُۥٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿١٨١﴾ فَمَنْ خَافَ مِن مُّوصٍ جَنَفًا أَوْ إِثْمًا فَأَصْلَحَ بَيْنَهُمْ فَلَآ إِثْمَ عَلَيْهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٨٢﴾

180. An wajabta muku, idan alamun mutuwa suka zo wa ɗayanku, idan har ya bar wani alheri (dukiya), to ya yi wasiyya ga mahaifa biyu da dangi mafiya kusanci, ta hanyar da ta dace (a shari'a). Haƙƙi ne tabbatacce a kan masu taƙawa.

181. To wanda ya canza shi (lamarin wasiyya) bayan ya ji shi, to lalle laifinsa yana kan waɗanda suka canza shi ne kawai. Lalle Allah Mai ji ne, Masani.
182. To duk wanda ya ji tsoron kaucewa bisa kuskure ko bisa zalunci daga mai yin wasiyya sai ya sasanta tsakaninsu (mai wasiyyar da waɗanda aka yi wa wasiyyar); to wannan babu laifi a kansa; lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyyana cewa, ya wajabta wa muminai idan ɗayansu ya ga alamun kusantowar mutuwa gare shi, kuma yana da dukiya, to ya yi wasiyya ga iyayensa da danginsa da wani kaso na wannan dukiyar tasa. Ya kuma yi wannan wasiyya yadda ya dace da adalci, ba tare da almubazzaranci ko rowa ba, ya yi la'akari da wanda ya fi kusanci da kuma wanda ya fi buƙata cikin waɗanda zai yi wa wasiyyar, sannan ba tare da ya cutar da magadansa ba. Allah ya nuna cewa, wannan al'amari kaƙƙi ne a kan duk masu taƙawa; masu kula da haƙƙokin wasu dake kansu.
Wasu daga cikin malamai suna ganin ayar rabon gado ta cikin *Suratun Nisa'i,* aya ta 11 ta shafe hukuncin wannan ayar.

Abu Umamatul Bahili (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana faɗa a huɗubarsa ta hajjin bankwana cewa: “Allah ya bai wa kowanne mai haƙƙi haƙƙinsa, don haka babu wasiyya ga mai cin gado”. [Abu Dawud#2870 da Tirmizi#2120].
Amma kuma wasu malaman suna ganin ba a shafe duk hukuncin ayar ba gaba ɗaya. Har yanzu tana nuna mahimmancin wasiyya ga makusanta waɗanda ba za su ci gadon wannan mamaci ba, to sai ya yi wasiyya da wani kaso daga cikin dukiyarsa bayan ya mutu, amma da sharaɗin kada kason ya wuce ɗaya bisa ukun dukiyar.
To bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna girman sha’anin wasiyya da wajabcinta, sai kuma ya gargaɗi wanda zai canja ta daga yadda aka bar masa ita, Allah ya bayyana cewa, duk wanda ya canja wasiyya daga yadda ya ji ta daga bakin mai wasiyya, ta hanyar ya ƙara ko ya rage daga abin da mamaci ya bar masa, to haƙiƙa ya ɗaukar wa kansa wani babban laifi, kuma babu wani laifi da zai shafi mamacin da ya bar masa wasiyyar a kan haka. Allah mai ji ne kuma masani ne zai yi wa kowa sakayya gwargadon aikinsa mai kyau ko mummuna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin wanda ya lura da cewa mai barin wasiyyar ya tabka kusukure a cikin wasiyyarsa, ya bai wa wani, ya hana wanda ya fi cancanta komai, ko ya ba wa mawadaci marar buƙata a cikin dangi, ya hana talaka mai tsananin buƙata a cikinsu, to a nan sai mai kula da wasiyya ya shiga tsakani ya sasanta dangin mamacin ya gyara kuskuren dake ƙunshe cikin wannan wasiyyar, to bai yi laifin komai ba, sai ma ladan sulhu da za a ba shi. Allah mai gafara ne ga waɗanda suka tuba, mai rahama ne gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babbar hikimar farlanta azumin Ramadan shi ne dacewa da taƙawa.

2. Tausayawar Ubangiji ga bayinsa da rahmarsa ta musamman ga wannan al’umma. Dubi yadda ya koro bayanin farlanta musu azumin Ramadan cikin wani salo na lallashi da kwantar da hankalinsu.
Na Farko: Ya fara da kiran su da mafi tsadar suna, wato ‘Ya ku waɗanda suka yi imani’.
Na Biyu: Ya nuna musu cewa ba su ne farkon al’umma da ya wajabta wa azumi ba, a’a, ya wajabta shi a kan al’ummun da suka gabace su. Wannan zai ƙara sa musu nutsuwa.
Na Uku: Ya bayyana musu babban tagomashi da yake cikin aiwatar da wannan farali, shi ne samun taƙawa.
Na Huɗu: Ya bayyana musu cewa, azumi ne na ‘yan kwanaki kaɗan, ba watanni ba.
Na Biyar: Ya yi rangwame ga mai larura da wanda zai wahala matuƙa wajen azumi da cewa, suna iya sha, su rama a wani lokacin daban. Wanda azumin yake yi masa wahala kuma, ya ciyar a madadin azumin.
Na Shida: Ya bayyana musu falalar watan da ya zaɓa musu don gudanar da wannan ibadar, irin abin da wata al’ummar ba ta samu ba.
Na Bakwai: Ya jaddada musu cewa yana nufin sauƙi gare su, ba tsanani ba.
Na Takwas: Ya sake fito musu da wata hikimar da take cikin wannan azumi, ita ce jaddada godiyarsu ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bisa ni’imominsa da yake yi musu, tare da kabarbari gare shi na girmamawa.

3. Waɗannan ayoyi suna tabbatar da ƙa’idar cewa a shari’a wahala tana jawo rangwame a hukunci.

4. Shigo da maganr addu’a yayin da ake zancen azumi yana nuna ya kamata bawa ya dage da addu’a a waɗannan kwanaki don neman falalar Ubangijinsa, kuma ana karɓar addu’ar mai azumi yayin da ya zo buɗa baki.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana nuna wa bayinsa cewa, shi kaɗai ya kamata a roƙa don neman biyan buƙata, kuma ba shi buƙatar kamun ƙafa da wani yayin roƙon Allah; ka roƙe shi kai-tsaye, yana jin ka, kuma yana ganin ka.

6. Yana daga cikin sharuɗɗan karɓar addu'ar bawa, shi ma ya amsa wa Allah nasa kiran, ta hanyar yi masa ɗa'a, da yi wa Manzonsa ɗa'a.

Suratul Baƙara (183-187)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُتِبَ عَلَيۡكُمُ ٱلصِّيَامُ كَمَا كُتِبَ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ١٨٣ أَيَّامٗا مَّعۡدُودَٰتٖۚ فَمَن كَانَ مِنكُم مَّرِيضًا أَوۡ عَلَىٰ سَفَرٖ فَعِدَّةٞ مِّنۡ أَيَّامٍ أُخَرَۚ وَعَلَى ٱلَّذِينَ يُطِيقُونَهُۥ فِدۡيَةٞ طَعَامُ مِسۡكِينٖۖ فَمَن تَطَوَّعَ خَيۡرٗا فَهُوَ خَيۡرٞ لَّهُۥۚ وَأَن تَصُومُواْ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ١٨٤ شَهۡرُ رَمَضَانَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ فِيهِ ٱلۡقُرۡءَانُ هُدٗى لِّلنَّاسِ وَبَيِّنَٰتٖ مِّنَ ٱلۡهُدَىٰ وَٱلۡفُرۡقَانِۚ فَمَن شَهِدَ مِنكُمُ ٱلشَّهۡرَ فَلۡيَصُمۡهُۖ وَمَن كَانَ مَرِيضًا أَوۡ عَلَىٰ سَفَرٖ فَعِدَّةٞ مِّنۡ أَيَّامٍ أُخَرَۗ يُرِيدُ ٱللَّهُ بِكُمُ ٱلۡيُسۡرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ ٱلۡعُسۡرَ وَلِتُكۡمِلُواْ ٱلۡعِدَّةَ وَلِتُكَبِّرُواْ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمۡ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٨٥ وَإِذَا سَأَلَكَ عِبَادِي عَنِّي فَإِنِّي قَرِيبٌۖ أُجِيبُ دَعۡوَةَ ٱلدَّاعِ إِذَا دَعَانِۖ فَلۡيَسۡتَجِيبُواْ لِي وَلۡيُؤۡمِنُواْ بِي لَعَلَّهُمۡ يَرۡشُدُونَ ١٨٦ أُحِلَّ لَكُمۡ لَيۡلَةَ ٱلصِّيَامِ ٱلرَّفَثُ إِلَىٰ نِسَآئِكُمۡۚ هُنَّ لِبَاسٞ لَّكُمۡ وَأَنتُمۡ لِبَاسٞ لَّهُنَّۗ عَلِمَ ٱللَّهُ أَنَّكُمۡ كُنتُمۡ تَخۡتَانُونَ أَنفُسَكُمۡ فَتَابَ عَلَيۡكُمۡ وَعَفَا عَنكُمۡۖ فَٱلۡـَٰٔنَ بَٰشِرُوهُنَّ وَٱبۡتَغُواْ مَا كَتَبَ ٱللَّهُ لَكُمۡۚ وَكُلُواْ وَٱشۡرَبُواْ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَكُمُ ٱلۡخَيۡطُ ٱلۡأَبۡيَضُ مِنَ ٱلۡخَيۡطِ ٱلۡأَسۡوَدِ مِنَ ٱلۡفَجۡرِۖ ثُمَّ أَتِمُّواْ ٱلصِّيَامَ إِلَى ٱلَّيۡلِۚ وَلَا تُبَٰشِرُوهُنَّ وَأَنتُمۡ عَٰكِفُونَ فِي ٱلۡمَسَٰجِدِۗ تِلۡكَ حُدُودُ ٱللَّهِ فَلَا تَقۡرَبُوهَاۗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ ءَايَٰتِهِۦ لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمۡ يَتَّقُونَ ١٨٧

183. Ya ku waɗanda suka yi imani, an wajabta muku azumi kamar yadda aka wajabta wa waɗanda suke gabaninku, don ku samu taƙawa.

184. Waɗansu kwanaki ne ƙididdigaggu. To duk wanda ya kasance marar lafiya a cikinku ko a kan wata tafiya, to (idan ya sha azumi) sai ya rama a waɗansu kwanakin na daban. Kuma waɗanda za su yi azumi da wahala su ba da fansa ta ciyar da miskini; to duk wanda ya ƙara (a kan abincin miskini), to wannan alheri ni gare shi. Amma ku yi azumin shi ne ya fi muku alheri, in har kun kusance kuna sani.

185. Watan Ramadan shi ne wanda aka saukar da Alƙur'ani a cikinsa, shiriya ne ga mutane kuma ayoyi ne bayyanannu na shiriya, kuma mai rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya). Don haka duk wanda ya halarci wannan watan daga cikinku, to ya azumce shi, kuma wanda ya kasance marar lafiya ko a kan wata tafiya, to (idan ya sha azumi) sai ya rama a waɗansu kwanakin na daban. Allah Yana nufin sauƙi a gare ku, kuma ba Ya nufin tsanani a gare ku, don ku cika adadin (kwanakin Ramadan), kuma domin ku girmama Allah bisa ga shiryar da ku da Ya yi, don ku yi godiya.
186. Kuma idan bayina sun tambaye ka game da Ni, to Ni kusa Nake (da su), Ina amsa kiran mai kira idan ya kiraye Ni; to su amsa Mini nawa kiran, kuma su yi imani da Ni, don su shiryu.

187. An halatta muku saduwa da matankU a daren azumi. Su sutura ne a gare ku, ku ma kuma sutura ne a gare su. Allah Ya san cewa ku lalle kun kasance kuna ha'intar kawunanku, sai Ya karɓi tubanku kuma Ya yi muku afuwa; to a yanzu ku sadu da su (da daddare), kuma ku nemi abin da Allah Ya rubuta muku, kuma ku ci, kuma ku sha har farin zare ya bayyana a gare ku daga baƙin zare na alfijir (wato ketowar Alfijir), sannan kuma ku cika azumi zuwa dare, kuma kar ku sadu da su alhali kuna i'itikafi a masallatai.

Waɗannan iyakoki ne na Allah, kada ku kusance su. Kamar haka ne Allah Yake bayyana ayoyinsa ga mutane, don su samu taƙawa.

A waɗannan ayoyi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin yadda ya wajabta wa wannan al'umma ibadar azumi, kamar yadda ya wajabta wa al'ummomin da suka gabace ta, domin hikimar yin hakan shi ne samun taƙawa.
Domin rahama ta Ubangiji da tausayawarsa ga bayinsa, bai umarce su da yin azumi na tsawon watanni ba, a'a, sai ya sanya shi tsawon 'yan kwanaki ne kaɗan. Bayan haka kuma, sai ya yi rangwame ga marar lafiyar da ba zai iya yin azumi ba da matafiyi da yake neman sauƙi cikin tafiyarsa da cewa, za su iya ajiye azumi, daga baya su rama a wasu kwanakin daban.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin wanda yake yin azumi da kyar cikin matsananciyar wahala, zai iya ciyar da mabuƙaci ɗaya a madadin kowace rana. Amma idan ya ga dama don raɗin kansa, yana iya ciyar da fiye da mabuƙaci ɗaya, to yin haka aikin alheri ne. Wasu masana tafsiri suna cewa, wannan gaɓar a wannan ayar ta yi nuni ne a kan cewa, an ba wa mutumin da zai iya azumi zaɓi na ya yi azumin ko ya sha, ya ciyar a madadinsa, daga baya aka shafe wannan hukunci na bayar da zaɓi, aka wajabta wa duk wani mai ikon azumtar watan Ramadana a ayar dake biye da wannan. Amma wasu masana suna ganin ayar tana nan ba a shafe ta ba, kuma tana magana ne a kan waɗanda yin azumi yake ba su wahala matuƙa kamar tsoho da tsohuwa tukub ko marar lafiyan da aka fitar da ƙaunar warkewarsa, koma mace mai ciki ko mai shayarwa waɗanda suke jiye wa kansu ko 'ya'yansu tsoro shiga mawuyacin hali idan sun yi azumi, to sai su sha azumin, su ciyar a madadinsa. Wannan fahimta ce ta wasu sahabbai da tabi'ai. [Duba Ibni Taimiyya, Sharhu Umdatul Fiƙh, 1:262-264].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana babbar falalar watan Ramadan da cewa, ita ce saukar da Alƙur'ani a cikinsa, Littafin da ya ƙunshi shiriya da fayyacewa tsakanin ƙarya da gaskiya ga mutane. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin wajabcin azumtar wannan wata mai daraja ga duk wanda ya riski watan yana zaune a gari, ba matafiyi ba. Amma idan mutum ba shi da lafiya ko yana cikin halin tafiya, to yana iya ajiye azumi, ya rama a wasu kwanakin daban. Wannan sauƙi ne daga Allah ga bayinsa, domin shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) har ko da yaushe mai son sauƙaƙawa ne gare su, ba mai son tsanantawa ba, domin bayinsa su zamanto masu gode masa game da ni'imar shiriya da ya yi musu da nusantar da su ga falalar wannan ibada, tare da sauƙaƙe musu hukunce-hukuncenta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya dawo da maganarsa zuwa ga Annabinsa (ﷺ) cewa, idan bayin Allah sun yi masa tambaya game da kusancin Allah gare su, to su sani cewa, Allah yana nan kusa da su, yana kuma amsa addu'ar duk wanda yake roƙon sa, don haka su abin da yake wajibi a kansu shi ne su amsa masa nasa kiran, su yi masa ɗa'a tare da miƙa wuya gare shi, da haka ne za su dace da gaskiya, sannan su sami cim ma buƙatunsu.
A farkon lokacin da aka wajabta azumi, an haramta wa Musulmi bayan sun yi barci da daddare, sannan suka farka, su ci ko su sha ko su sadu da matansu. Sai bin wannan doka ta zama da wahala a wurin wasu, sai Allah ya sassauta musu ita da cewa, ya halatta musu saduwa da matansu a cikin daren Ramadan, kamar yadda ya halatta musu su ci su sha a cikinsa, har zuwa hudowar alfijir.
Albara'u ɗan Azib (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: "Sahabban Annabi (ﷺ) sun kasance idan ɗayansu yana azumi, sai ya yi barci kafin ya yi buɗa baki, to ba shi da damar idan ya farka cikin dare ya ci ko ya sha wani abu, har sai kashe-gari bayan faɗuwar rana. Sai wata rana wani sahabi mutumin Madina, ana kiran sa Kaisu ɗan Sirma, yana azumi, da lokacin buɗa baki ya yi, ya zo gida ya tambayi matarsa, ko tana da abinci? Sai ta ce: 'A'a, amma bari in je in nemo maka.' To shi kuma ya yini yana aiki, ya gaji, sai barci ya ɗauke shi. Matar ta dawo yana barci, sai ta ce: 'Ka shiga uku.' Ya wayi gari, ya yini bai ci komai ba. Da rana ta take tsaka, sai kawai ya faɗi ya suma; sai aka je aka faɗa wa Annabi (ﷺ) abin da ya faru, sai wannan ayar ta sauka: 'An halatta muku saduwa da matanku a daren azumi....' Sahabbai suka yi farin ciki da haka sosai. Sannan kuma ɗaya ɓangaren ayar ya sauka tana cewa: '....kuma ku ci, kuma ku sha har farin zare ya bayyana na alfijir....'

Game da faɗar Allah cewa: “....Allah ya san cewa kun kasance kuna ha’intar kawukanku....”, Albara’u ɗan Azib yana cewa: “Yayin da aka wajabta azumtar watan Ramadan, sahabbai ba su da damar kusantar iyalansu a tsawon watan gaba ɗaya, sai ya zamanto wasu mazajen suna yin ha’inci, sai Allah ya saukar da aya mai cewa: “....Allah ya san cewa, lalle kun kasance kuna ha’intar kawukanku....” [Bukhari #4508].
Game da faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): “....ku ci, ku sha har farin zare ya bayyana daga baƙin zare na alfijir....”, Sahlu bn Sa’ad (Allah ya kara masa yarda) yayin da ayar ta fara sauka, babu ambaton kalmar ‘alfijir’ a cikinta, sai ya zamanto duk lokacin da wani zai yi azumi, sai ya ɗaura farin zare da baƙin zare a ƙafafuwansa, sai ya yi ta ci, yana sha abinsa, har sai lokacin da zai iya tantace tsakaninsu, sai Allah ya saukar da ƙarin ‘na alfijir’, daga lokacin sai suka fahinci ashe ana nufin dare ne da yini. [Bukhari #1917, da Muslim #1091].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana masu i’itikafi saduwa da matansu lokacin da suke cikin ibadar i’itikafi a masallaci, yana mai ƙara bayyana musu cewa duk waɗannan abubuwan da ya hana mai yin azumi da mai i’itikafi aikatawa dokoki ne na Allah, kada su kuskura su keta su. To kamar yadda Allah ya yi cikakken bayani dangane da hukunce-hukuncen azumi, haka ne yake bayyana sauran hukunce-hukuncen shari’a a wannan Littafi nasa, da kuma a kan harshen Manzonsa (ﷺ), domin mutane su gane yadda ya kamata su yi wa Allah ɗa’a, wajen aikata wajibai, da guje wa abubuwan da aka haramta.

Suratul Baƙara (188)

وَلَا تَأۡكُلُوٓاْ أَمۡوَٰلَكُم بَيۡنَكُم بِٱلۡبَٰطِلِ وَتُدۡلُواْ بِهَآ إِلَى ٱلۡحُكَّامِ لِتَأۡكُلُواْ فَرِيقٗا مِّنۡ أَمۡوَٰلِ ٱلنَّاسِ بِٱلۡإِثۡمِ وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ١٨٨

188. Kuma kada ku ci dukiyoyinku a tsakaninku ta hanyar rashin gaskiya, haka kuma kada ku miƙa dukiyoyinku zuwa ga masu shari’a, don kawai ku ci wani ɓangare na dukiyar mutane ta hanyar saɓo, alhali kuna sane.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi gargaɗi ga mai da gangancin saba wa hukunce-hukuncen azumi, ya ce waɗannan iyakokin Allah ne kada wani ya kuskura ya kusance su balle ya ƙetare su, sai kuma ya biyo bayansu da bayanin wani hukunci na bai-ɗaya, wanda shi ne haramcin cin dukiyar mutane ba tare da wani haƙƙi ba. Wannan doka ce mai shiga cikin hukunce-hukunce da yawa. Sannan sai ya yi wani hani a keɓance, watau shi ne haramcin bayar da cin hanci ga alƙalai ko mahukunta don su bayar da damar cin dukiyar wani ba a kan gaskiya ba, kamar mutumin da ake bi bashi, mai kuɗin kuma ba shi da wata bayyananniyar sheda a kan wannan bashi, sai ya musanta bashin da ke kansa, alhalin ya san gaskiya ne, idan an je gaban alƙali sai ya ba da cin hanci domin ya danne wannan haƙƙi da ke kansa ya cinye dukiyar ɗan’uwansa ba bisa gaskiya ba, alhali yana sane.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abin da duk shari’a ba ta yarda da shi ba, to al’ada ba za ta mayar da shi halattace ba.

2. Duk abin da mutum zai nufi cim masa to ya bi ta hanyar da ta dace kuma ta inda ake bi a cim ma samun wannan abu.

3. Falalar taƙawa, domin mai taƙawa yana tare da Allah cikin taimakon sa da ba shi nasara da ƙarfafar sa.

4. Bai halatta garin ɗaukar fansa mutum ya zarce abin da aka yi masa ba na zalunci, idan har ya yi haka to ya zama shi ne azzalumin.

5. Sharɗanta ɗaukar fansa da cewa, lalle ta kasance gwargwadon yadda aka yi wa mutum yana nuna kwaɗaitarwa a kan ya yafe domin gudun kada ya zarce yadda aka yi masa ya samu kansa cikin azzalumai.

6. Muhimmacin ciyar da dukiya wajen taimakon addinin Musulunci da taimaka wa Musulmi mabuƙata da tanadar musu duk wani abu na alheri da zai ƙara musu ƙarfi wajen tunkarar maƙiyansu.

Suratul Baƙara (189-195)

۞ يَسۡـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلۡأَهِلَّةِۖ قُلۡ هِيَ مَوَٰقِيتُ لِلنَّاسِ وَٱلۡحَجِّۗ وَلَيۡسَ ٱلۡبِرُّ بِأَن تَأۡتُواْ ٱلۡبُيُوتَ مِن ظُهُورِهَا وَلَٰكِنَّ ٱلۡبِرَّ مَنِ ٱتَّقَىٰۗ وَأۡتُواْ ٱلۡبُيُوتَ مِنۡ أَبۡوَٰبِهَاۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ١٨٩ وَقَٰتِلُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ ٱلَّذِينَ يُقَٰتِلُونَكُمۡ وَلَا تَعۡتَدُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُعۡتَدِينَ ١٩٠ وَٱقۡتُلُوهُمۡ حَيۡثُ ثَقِفۡتُمُوهُمۡ وَأَخۡرِجُوهُم مِّنۡ حَيۡثُ أَخۡرَجُوكُمۡۚ وَٱلۡفِتۡنَةُ أَشَدُّ مِنَ ٱلۡقَتۡلِۚ وَلَا تُقَٰتِلُوهُمۡ عِندَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِ حَتَّىٰ يُقَٰتِلُوكُمۡ فِيهِۖ فَإِن قَٰتَلُوكُمۡ فَٱقۡتُلُوهُمۡۗ كَذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلۡكَٰفِرِينَ ١٩١ فَإِنِ ٱنتَهَوۡاْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٩٢ وَقَٰتِلُوهُمۡ حَتَّىٰ لَا تَكُونَ فِتۡنَةٞ وَيَكُونَ ٱلدِّينُ لِلَّهِۖ فَإِنِ ٱنتَهَوۡاْ فَلَا عُدۡوَٰنَ إِلَّا عَلَى ٱلظَّٰلِمِينَ ١٩٣ ٱلشَّهۡرُ ٱلۡحَرَامُ بِٱلشَّهۡرِ ٱلۡحَرَامِ وَٱلۡحُرُمَٰتُ قِصَاصٞۚ فَمَنِ ٱعۡتَدَىٰ عَلَيۡكُمۡ فَٱعۡتَدُواْ عَلَيۡهِ بِمِثۡلِ مَا ٱعۡتَدَىٰ عَلَيۡكُمۡۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلۡمُتَّقِينَ ١٩٤ وَأَنفِقُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا تُلۡقُواْ بِأَيۡدِيكُمۡ إِلَى ٱلتَّهۡلُكَةِ وَأَحۡسِنُوٓاْۛ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٩٥

189. Suna tambayar ka dangane da jirajiran wata. Ka ce: “Su lokuta ne (don amfani) ga mutane da (tantance lokacin) Hajji." Kuma ba ya daga cikin aikin ɗa'a, ku zo wa gidaje ta bayansu, sai dai mai aikin ɗa'a shi ne wanda ya yi taƙawa. Kuma ku shigo wa gidajen ta ƙofofinsu, kuma ku kiyaye dokokin Allah don ku rabauta.

190. Kuma ku yaƙi waɗanda suke yaƙar ku don ku ɗaukaka kalmar Allah, kuma kada ku ƙetare iyaka. Lalle Allah ba Ya son masu ƙetare iyaka.

191. Kuma ku yaƙe su duk inda kuka same su, kuma ku fitar da su ta inda suka fitar da ku; kuma fitina (ta kafirci) ita ce mafi tsanani fiye da kisa, kuma kada ku yaƙe su a wurin Masallaci mai alfarma, har sai idan sun yaƙe ku a cikinsa, idan har suka yaƙe ku, to ku ma ku yaƙe su. Kamar haka ne sakamakon kafirai yake.

192. Amma idan suka daina, to lalle Allah Mai yawan gafara ne, Mai jin ƙai.

193. Kuma ku yaƙe su har ya zamanto ba a sami wata fitina ba, kuma addini ya zamo na Allah ne. Idan suka daina, to babu sauran kai farmaki sai a kan azzalumai.

194. (Idan sun yaƙe ku a) wata mai alfarma, (ku ma ku yaƙe su a) wata mai alfarma, kuma a cikin abubuwa masu alfarma akwai ƙisasi. Don haka duk wanda ya yi muku ta'addanci, to ku ma ku rama ta'addancin gwargwadon yadda ya yi muku ta'addanci; kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani lalle Allah Yana tare da masu taƙawa.

195. Kuma ku ciyar da dukiyoyinku domin taimakon addinin Allah, kuma kada ku jefa kawunanku zuwa ga halaka, kuma ku kyautata; lalle Allah Yana son masu kyautatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin hikimar da ke cikin halittar jinjirin wata tun yana ƙarami har ya girma ya cika. Wasu sahabban Annabi (ﷺ) sun yi masa tambaya cewa, mene ne hikimar da take cikin yin hakan? Me ya sa kuma watanni aikinsu ba ya kama da na rana wajen fitowa gaba ɗaya bisa kamanni guda, sai dai su riƙa caccanzawa daga ƙanƙanta har su girma, sannan kuma su dawo suna raguwa har kuma su ɓuya? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ba su amsar cewa, Allah ya yi haka ne domin waɗannan watanni su zama lokutan gane al'amuran ibadunsu, kamar Hajji da azumi da idodi da kuma kiyaye lokutan al'amuransu na yau da kullum da yarjejeniya da za ta shigo tsakaninsu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana a kan wata al'ada marar ma'ana ta Larabawa yayin fita zuwa aikin Hajji ko dawowa lokacin da mutum ya sanya ihrami sai ya haramta wa kansa shiga gidansa ta ƙofar gida. Idan ya buƙaci shiga to sai dai ya hauro ta bayan gidan. Suna yin haka ne kuma da sunan bautar Allah da neman lada a wurinsa. Wata rana wani mutumin Madina ya dawo daga Hajji sai ya shiga gidansa ta ƙofar gida, sai hakan ya zama abin magana a cikin jama'a, aka riƙa sukan wannan mutum, sai Allah ya saukar da wannan ayar, yana faɗa wa muminai cewa, wannan al'ada ta haurowa ta bayan gida, ba ita ce aikin alheri ba a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Aikin alheri a wurinsa shi ne mutum ya kiyaye dokokinsa ta hanyar aikata umarninsa da barin haninsa. Don haka daga yanzu kowa ya dinga shiga gidansa ta ƙofar gidan ba ta baya ba. Kuma su lizimci taƙawa, domin da ita ne za su cim ma buƙatarsu ta samun rabauta a wurin Allah.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su yaƙi duk kafirin da ya fito yana yaƙar su. Kuma su tsarkake niyyarsu da yi domin Allah kawai, don haka kada su kuskura su yi ta'addanci wajen mayar da martani a kan kafiran da suke yaƙar su. Wato kar su riƙa kashe musu mata da yara da tsofaffi da sauran waɗanda ba su shiga yaƙi da su ba; aikata hakan ta'addanci ne, Allah kuwa ba ya son 'yan ta'adda masu zarce haƙƙinsu.

Annabi (ﷺ) ya kasance idan ya shirya rundunar yaƙi yakan yi wasiyya ga shugaban wannan runduna da mayaƙansa ya ce musu: "Ku yi yaƙi da sunan Allah kuma don Allah, ku yaƙi wanda ya kafirce wa Allah, ku yi yaƙi, kada ku riƙa satar ganima, kuma kada ku riƙa yin yaudara kuma kada ku riƙa yin gunduwa-gunduwa da gawarwakin abokan faɗanku, kada kuma ku kashe yara. Idan kun haɗu da maƙiyanku mushrikai, to ku kirawo su zuwa ga abubuwa guda uku; kowane ɗaya daga cikin ukun suka amsa muku; to ku karɓa daga wajensu, ku fasa yaƙar su." [Muslim #1731].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su yaƙi kafiran da suke yaƙar su a duk inda suka haɗu da su, sannan su ma muminai su kore su daga garuruwan da su kafiran suka kore su a baya. Shirkar da suke ciki ta fi kisansu girma a wurin Allah. Hakanan abin da kafirai suke yi wa muminai na hana su addininsu shi ma ya fi kisa muni a wurin Allah, domin zafin kisa taƙaitacce ne, amma zafin azabar kafirci mai ɗorewa ne har abada.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana muminai fara kai wa kafirai hari a masallaci mai alfarma na Makka; amma kuma idan kafiran su ne suka fara kawo musu hari a wannan wuri mai tsarki, to lalle muminai su mayar musu da martani, kuma suna iya kashe su a wannan wuri domin nuna musu sakamakon ta'addancinsu. Amma idan sun tuba sun musulunta sun bar yaƙar su to su sani cewa, Allah mai gafarta musu duk laifukansu da suka wuce, kuma zai yi musu rahama ya datar da su ga samun duk wani alheri na duniya da lahira.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya maimaita umarnin yaƙar mushrikai har a kai ga murƙushe bautar wanin Allah gaba ɗaya, addini da bauta su zama na Allah ne shi kaɗai, muddun dai su mushrikan za su ci gaba da yaƙar su; to amma idan sun rabu da su sun daina yaƙar su, sun tuba zuwa ga Allah to wajibi ne kuma su muminai su daina yaƙar su, domin wanda ya cancanta a yaƙa shi ne azzalumi mai cutar da muminai da kafircinsa da shirkarsa.

Sai kuma Allah ya bayyana hukuncin yaƙar kafirai 'yan ta'adda a cikin wata mai alfarma yayin da su suka fara yaƙar muminai a cikinsa. Allah ya halatta wa muminai yaƙar su matuƙar sun yaƙe su a cikin wannan watan; kamar yadda suka keta alfarmar watanni masu alfarma, to a bi su da ɗaukar fansa ta hanyar keta

musu irin waɗannan watannin masu alfarma a yaƙe su a cikinsu; wannan shi ne sakamako na adalci, wanda duk ya yi ma muminai ta'addanci to su mayar masa da martani gwargwadon irin ta'addancinsa. To amma sai Allah ya umarci muminai da su kiyaye dokokin Allah kada su yi ramuwa da abin da ya fi ta'addancin da aka yi musu muni. Su kiyaye dokokin Allah domin yin haka shi zai sa su zama tare da Allah, domin yana tare da duk wani mai bin umarninsa ya guji haninsa.
Daga nan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da ciyar da dukiya saboda shi don ɗaukaka addininsa, ya gargaɗi muminai da su guji jefa kansu cikin halaka ta hanayar barin umarninsa ko aikata abin da ya hana, kamar rowa da ƙin bayar da taimako wajen gina addinin Allah ko ba shi kariya daga maƙiyansa. Ya umarce su su zama masu kyautatawa a ko da yaushe tare da kowa domin Allah yana son mutane masu kyautatawa.

An karɓo daga Abu Ayyuba Al-Ansari (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Mun kasance wata rana a birnin Rum, sai mayaƙan Rumawa masu yawa suka fito mana, sai mayaƙan Musulmi kwatankwacinsu ko fiye da su a yawa su ma suka fita taren su. Uƙba bn Amir yana jagorantar mutanen Misra, mutanen Madina kuwa Fadhalatu bn Ubaid ne yake jagorantar su. Sai wani Musulmi ya kutsa cikin rudunar Rumawa har sai da ya shiga tsakiyarsu, sai Musulmi suka riƙa yi masa hargowa suna cewa, yaya zai jefa kansa cikin halaka? Sai Abu Ayyuba Al-Ansari ya tashi ya ce: "Ya ku mutane, kuna yi wa wannan ayar irin wannan fassarar, alhalin wannan ayar a kanmu mu mutanen Madina ta sauka. Lokacin da Musulunci ya yi ƙarfi ya samu mataimaka da yawa, sai waɗansu daga cikinmu suka riƙa faɗa wa 'yan'uwansu a ɓoye Annabi (ﷺ) bai sani ba, suna cewa: "Duk mun kashe dukiyoyinmu, ga shi yanzu Musulunci ya yi ƙarfi, kuma masu taimaka masa sun ƙara yawa, me zai hana mu yi zamanmu mu kula da farfaɗo da dukiyoyinmu da suka salwanta?! Sai Allah ya saukar da wannan ayar ga Annabinsa (ﷺ) domin mayar mana da martani a kan abin da muka faɗa wa juna, Allah ya ce: "Ku ciyar don Allah kada ku jefa kawunanku a cikin halaka." Don haka abin da ake nufi da halaka a nan shi ne, barin fita yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah da zama a gida don kula da dukiya da gyaranta." Wannan ta sa Abu Ayyuba Al-Ansari bai gushe ba yana fagen fama don ɗaukaka addinin Allah har ya rasu aka binne shi a ƙasar Rumawa." [Tirmizi #2974, Nasa'i *As-Sunan Al-Kubra* #11029].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yin kowane aiki don Allah ba don wani ya gani ya yaba ba.

2. Sauƙin da yake tattare a shari'ar Musulunci, don haka ne da aka tashi bayar da zaɓin nau'ukan kaffara da mai aikata wani abu da aka hana mahajjaci ko mai umara aikatawa, idan ya yi su cikin lalura, sai aka fara da ambaton kaffara mafi sauƙi ita ce azumi, sannan sai sadaka sannan sai yanka. Amma da aka ambaci azumin wanda ya yi hajjin *Tamattu'i ko* na *Kirani* kuma ba zai iya yanka ba, sai aka ce ya yi azumi uku a Hajji, bakwai kuma sai ya koma garinsu.

3. Taƙawa ita ce babbar guzurin zukata, da ita ne bawa yake samun tsira duniya da lahira.

4. Masu hankali cikin bayin Allah su ne suka san muhimmacin taƙawa da amfaninta a rayuwar bawa. Rashin taƙawa ga bawa alama ce da ke nuna rashin hankalinsa, kamar yadda rauninta alama ce da ke nuna raunin hankali.

5. Tuna wa mutum asalinsa kafin ni'imar Allah da falalarsa ta riske shi zai ƙara masa fahimtar girman ni'imar da Allah ya yi masa, ya gode masa.

6. Musulunci ba ya buƙatar Musulmai su yi watsi da sha’anin duniya domin Allah ya halicce su ne don su zama masu maye gurbin juna a bayan ƙasa, sai kuma ya umarce su da su yi aiki da dokokinsa wajen raya duniya, kada su yarda su kulle kawunansu a cikin kurkukunta su manta da gidan ƙarshe, gidan dawwama wanda shi ne lahira.

Suratul Baƙara (196-202)

وَأَتِمُّواْ ٱلۡحَجَّ وَٱلۡعُمۡرَةَ لِلَّهِۚ فَإِنۡ أُحۡصِرۡتُمۡ فَمَا ٱسۡتَيۡسَرَ مِنَ ٱلۡهَدۡيِۖ وَلَا تَحۡلِقُواْ رُءُوسَكُمۡ حَتَّىٰ يَبۡلُغَ ٱلۡهَدۡيُ مَحِلَّهُۥۚ فَمَن كَانَ مِنكُم مَّرِيضًا أَوۡ بِهِۦٓ أَذٗى مِّن رَّأۡسِهِۦ فَفِدۡيَةٞ مِّن صِيَامٍ أَوۡ صَدَقَةٍ أَوۡ نُسُكٖۚ فَإِذَآ أَمِنتُمۡ فَمَن تَمَتَّعَ بِٱلۡعُمۡرَةِ إِلَى ٱلۡحَجِّ فَمَا ٱسۡتَيۡسَرَ مِنَ ٱلۡهَدۡيِۚ فَمَن لَّمۡ يَجِدۡ فَصِيَامُ ثَلَٰثَةِ أَيَّامٖ فِي ٱلۡحَجِّ وَسَبۡعَةٍ إِذَا رَجَعۡتُمۡۗ تِلۡكَ عَشَرَةٞ كَامِلَةٞۗ ذَٰلِكَ لِمَن لَّمۡ يَكُنۡ أَهۡلُهُۥ حَاضِرِي ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ١٩٦ ٱلۡحَجُّ أَشۡهُرٞ مَّعۡلُومَٰتٞۚ فَمَن فَرَضَ فِيهِنَّ ٱلۡحَجَّ فَلَا رَفَثَ وَلَا فُسُوقَ وَلَا جِدَالَ فِي ٱلۡحَجِّۗ وَمَا تَفۡعَلُواْ مِنۡ خَيۡرٖ يَعۡلَمۡهُ ٱللَّهُۗ وَتَزَوَّدُواْ فَإِنَّ خَيۡرَ ٱلزَّادِ ٱلتَّقۡوَىٰۚ وَٱتَّقُونِ يَٰٓأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ١٩٧ لَيۡسَ عَلَيۡكُمۡ جُنَاحٌ أَن تَبۡتَغُواْ فَضۡلٗا مِّن رَّبِّكُمۡۚ فَإِذَآ أَفَضۡتُم مِّنۡ عَرَفَٰتٖ فَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ عِندَ ٱلۡمَشۡعَرِ ٱلۡحَرَامِۖ وَٱذۡكُرُوهُ كَمَا هَدَىٰكُمۡ وَإِن كُنتُم مِّن قَبۡلِهِۦ لَمِنَ ٱلضَّآلِّينَ١٩٨ ثُمَّ أَفِيضُواْ مِنۡ حَيۡثُ أَفَاضَ ٱلنَّاسُ وَٱسۡتَغۡفِرُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٩٩ فَإِذَا قَضَيۡتُم مَّنَاسِكَكُمۡ فَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ كَذِكۡرِكُمۡ ءَابَآءَكُمۡ أَوۡ أَشَدَّ ذِكۡرٗاۗ فَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَقُولُ رَبَّنَآ ءَاتِنَا فِي ٱلدُّنۡيَا وَمَا لَهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنۡ خَلَٰقٖ ٢٠٠ وَمِنۡهُم مَّن يَقُولُ رَبَّنَآ ءَاتِنَا فِي ٱلدُّنۡيَا حَسَنَةٗ وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِ حَسَنَةٗ وَقِنَا عَذَابَ ٱلنَّارِ٢٠١ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ نَصِيبٞ مِّمَّا كَسَبُواْۚ وَٱللَّهُ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ٢٠٢

196. Kuma ku cika aikin Hajji da umara domin Allah. To idan an tsare ku, sai ku gabatar da abin da ya sawwaƙa na hadaya, kuma kada ku aske kawunanku har sai hadaya ta kai wurin yankanta. To wanda ya kasance a cikinku mara lafiya ko akwai wata cuta a kansa, (idan yayi aski) to sai ya yi fidiya ta (hanyar) yin azumi ko sadaƙa ko yanka. Idan kuwa kun amintu, to duk wanda ya yi tamattu'i da yin umara tare da Hajji, to sai ya yanka abin da ya sawwaƙa na hadaya; amma wanda bai samu ba, sai ya yi azumin kwana uku a lokacin aikin Hajji, da kuma na kwana bakwai idan kun dawo gida. Waɗannan kwana goma ke nan cikakku. Wannan hukuncin yana ga wanda iyalinsa ba sa cikin hurumin Makka ne. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, ku sani cewa, lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne.

197. (Lokacin) hajji wasu watanni ne sanannu. Don haka duk wanda ya wajabta wa kansa aikin Hajji cikin waɗannan (watanni), to babu maganar saduwa da mace, kuma babu fasiƙanci, kuma babu jayayya a cikin aikin Hajji. Kuma duk abin da kuka aikata na alheri, Allah Yana sane da shi. Kuma ku yi guzuri, amma mafificin guzuri shi ne taƙawa, kuma ku kiyaye dokokina ya ku ma'abota hankula.

198. Babu wani laifi gare ku ku nemi falala daga Ubangijinku, don haka idan kun gangaro daga Arfa, to ku ambaci Allah a wurin (da ake kira) *Mash'arul Haraam,* kuma ku ambace Shi kamar yadda Ya shiryar da ku, ko da yake a da tabbas kun kasance daga cikin ɓatattu.
199. Sannan kuma sai ku gangaro ta inda mutane suka gangaro kuma ku nemi gafarar Allah; lalle Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.

200. To idan kun gama ayyukanku na Hajji, to ku yi ta ambaton Allah kamar yadda kuke ambaton iyayenku, ko ambaton Allah ya fi yawa. To daga cikin mutane akwai wanda yake cewa: “Ya Ubangijimu, Ka ba mu (rabo) a nan duniya”, kuma a lahira ba shi da wani rabo.

201. Kuma daga cikinsu akwai wanda yake cewa: “Ya Ubangijinmu, Ka ba mu kyakkyawa a nan duniya, kuma Ka ba mu kyakkyawa a lahira, Ka kuma tsare mu daga azabar wuta.”

202. Waɗannan suna da babban rabo na daga abin da suka aikata, kuma Allah Mai gaggawar hisabi ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin hukunce-hukuncen Hajji da umara a cikinsu, ya umarci waɗanda suka shiga haramin aikin Hajji ko umara da su cika aikinsu da rukunansa da wajibansa, kuma su yi shi don Allah ba don wani ba. Idan wani abu ko wasu suka hana su kaiwa ga Ɗakin Allah, kamar tsoro ko rashin lafiya ko wani dalili daban, to sai su yanka abin da Allah ya hore musu na raƙuma ko shanu ko tumaki. Kuma ya umarce su da kada su cire haraminsu idan wani abu ya tsare su har sai abin hadayarsu ya kai ga isa wurin da aka tsare su. Idan kuma ba wanda aka tsare ba ne to zai yanka hadayarsa ne a Haramin Makka. Idan na Hajji ne zai yanka shi ranar salla, wato goma ga Zulhijja. Wanda ya haɗu da rashin lafiya ko kwarkwata ta dame shi a kansa ya zama cikin buƙatar ya aske kansa, to yana iya askewa, to amma bayan ya aske zai yi azumin kwana uku, ko ya ciyar da miskini shida kowane cikinsu ya ba shi rabin mudu ko ya yanka akuya.
Idan matsala ta kau ta rashin samun shiga garin Makka, maniyyata suka samu isa Ɗakin Allah to duk wani maniyyaci da ya ɗauko umara kaɗai ya gama ta kuma yana niyar zai shiga aikin Hajji, to wajibi ne zai yi hadaya da abin da Allah ya hore masa cikin raƙuma ko shanu ko ƙananan dabbobi. Hakanan hukuncin yake ga mutumin da ya yi hajjin *Kirani,* wato ya haɗa umara da Hajji a niyya ɗaya. Idan kuwa wani ba shi da ikon yin yanka na hadaya to sai ya yi azumin kwana uku a lokacin Hajji, sannan bayan ya gama aikin hajjinsa ya dawo garinsu sai ya yi azumin kwana bakwai.
To wannan hukunci da aka ambata a nan ya shafi wanda ba mazaunin garin Makka ba ne, domin su ba su da hukuncin Hajji na *Tamattu*’i. Sannan sai Allah ya yi umarnin da yin taƙawa ta hanyar aikata abin da aka wajabta masa da kuma barin abin da aka hana shi, kuma ya tunatar da bayinsa cewa, su sani shi mai tsananin uƙuba ne ga duk wanda ya saɓa masa, ya aikata abin da ya hana.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana watannin Hajji da cewa, watanni ne sanannu, watau watan Shawwal, Zulƙi’ida da Zulhijja. To duk wanda ya ƙulla niyyar Hajji a cikin waɗannan watanni, dole ne ya nisanci kusantar mata da maganganu na kwarkwasa, ya nisanci duk wani aikin saɓon Allah, wanda ya haɗa har da abubuwan da aka hana shi aikata su lokacin da yake cikin harami, da zagin Musulmi, ya kuma guji jayayya ba bisa gaskiya ba.
Annabi (ﷺ) yana cewa: “Duk wanda ya yi Hajji don Allah, bai yi batsa ba, bai yi fasiƙanci ba, to zai koma kamar ranar da mahaifiyarsa ta haife shi.” [Bukhari #1521, da Muslim #1350].
Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya kwaɗaitar da su kan aikin alheri ya bayyana musu cewa, duk abin da bayinsa suka gabatar na alheri kaɗan ne ko mai yawa, to za su ga sakamakonsa a wurin Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci masu zuwa Hajji da su yi guzuri na abin da za su buƙata a wannan tafiyar tasu domin kada su je suna roƙon mutane abin hannunsu. To amma duk da haka sai Allah ya nuna musu cewa guzurin da ya fi kowane muhimmanci shi ne guzurin taƙawa domin ita ce abincin zukata, da ita ne ake samun jin daɗi na har abada.
Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Mutanen Yamen sun kasance suna zuwa aikin Hajji ba guzuri, sai su ce su masu dogaro ga Allah ne. amma idan sun iso garin Makka sai su riƙa roƙon mutane. Sai Allah ya saukar da faɗarsa: (kuma ku yi guzuri, amma mafificin guzuri shi ne taƙawa).”
Sannan Allah ya umarci masu hankali da ita wannan taƙawar domin su ne suka san amfaninta da muhimmancinta fiye da kowa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin wasu daga cikin ayyukan Hajji. Allah ya bayyana wa mahajjata cewa, babu laifi don sun zo aikin Hajji sun yi wani abu na kasuwancinsu. Abdullah ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: “Akwai wasu kasuwanni da suke ci tun a lokacin jahiliyya a lokacin aikin Hajji watau kasuwar Ukaza da Majanna da kuma Zulmajaz. Lokacin da Musulunci

ya zo sai Musulmi suka riƙa jin kamar laifi ne su ci gaba da cin waɗannan kasuwanni a lokutan aikin Hajji, sai Allah ya saukar da wannan ayar." [Bukhari #2050]. Ya umarci mahajjata idan sun baro Arfa sun iso Muzdalifa su ambaci Allah a wurin. Wannan ambaton Allah da aka yi umarni da shi a nan ya ƙunshi har da salla da addu'a a wurin. Kuma su ambace shi, su tuna shiriyar da ya yi musu ta hanya madaidaiciya bayan a da sun kasance a cikin mabayyaniyar ɓata.
Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Kuraishawa waɗanda ba sa yin tsayuwar Arfa kamar yadda sauran ƙabilu suke tsayuwa, watau iyakarsu Muzdalifa sai su juyo. Sai Allah ya umarce su a nan cewa, su ma su je su tsaya a Arfa tare da sauran mutane sannan idan lokacin barin Arfa ya yi su shigo tare da sauran jama'a su taho Muzdalifa. Allah kuma ya umarci alhazai da su nemi gafarar Allah a kan zunubansu, domin shi Allah mai yin gafara ne ga duk wanda ya neme ta a wajensa mai rahama ne ga bayinsa muminai.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci alhazai da cewa, idan sun kammala ayyukan hajjinsu sun sauke harami, to su yawaita ambaton Allah (Mai tsarki da ɗaukaka),kamar yadda suke ambaton iyayensu, kai su ambace shi fiye ma da yadda suke ambaton iyayensu.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci alhazai da yawan ambatonsa sai kuma ya umarce su da addu'a domin wannan lokaci ne da ya dace a karɓa addu'o'insu. Sannan Allah ya zargi wanda idan yana addu'a duniya kaɗai yake roƙa, ba shi da wani rabo a lahira. Sai kuma ya yabi muminai masu roƙon Allah ya ba su alherin duniya da na lahira, kuma ya kare su daga azabar wuta ta lahira. To irin waɗannan bayi na Allah su ne suke samun babban sakamako a kan aikinsu na Hajji da suka yi, sannan a lahira Allah ya datar da su samun alherin da suka roƙa. Allah mai gaggawa ne wajen lissafin ayyukan bayinsa kuma mai gaggawa ne wajen yi musu sakamako.
Daga nan sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mahajjata da yin kabarbari a ranakun zaman Mina, wato "*Ayyamut tashriƙ*", waɗanda su ne ranar sha ɗaya da sha biyu da sha uku na watan Zulhijja. Waɗannan kabarbari sun haɗa har da kabbarar ranar sallar layya, sannan da sauran kabarbari a sauran kwanaki na lokuta daban-daban.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa babu laifi a kan mahajjaci ya bar Mina a rana ta goma sha biyu ko ya jinkirta fita har zuwa rana ta goma sha uku domin ya yi jifa a wannan ranar, duk mutum na da zaɓi a nan, matuƙar dai ya kiyaye dokokin Allah ya aikata abin da ya umarce shi da shi ya kauce wa abin da ya hana shi. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wasiyya ga bayinsa da taƙawa, kuma su tabbatar da cewa, za a taru a gabansa ranar gobe ƙiyama domin yi musu hisabi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Illar yawan musu da jayayya. Yawan jayayya da yawan musu ba sa haifar da wani alheri ga masu yin su.

2. Gargaɗi game da watsi da nasihar masu nasiha ko wa'azin masu wa'azi. Duk wanda yake watsi da maganar masu yi masa nasiha a kan jin tsoron Allah to wannan ya yi kama da munafuƙai a cikin ayyukansu.

3. Girman kai yana gadar wa da mai shi rashin tsoron Allah.
4. Duk kyan maganar baki idan aiki ya saɓa da ita, to ba ta da wani amfani ga mai yin ta.

5. Yardaddu a wurin Allah su ne waɗanda suka sayar da rayuwarsu gaba ɗaya ga Allah, don neman yardarsa da gwaggwaɓar lada a wajensa.

6. Allah yana son wasu bayinsa, kuma yana ƙin wasu, don haka ya siffantu da siffar 'Soyayya'.

7. Allah yana yarda da wasu zaɓaɓɓu daga cikin bayinsa, don haka ne ya siffantu da siffar ‘Yarda’.

Suratul Baƙara (203-207)

* وَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ فِيٓ أَيَّامٖ مَّعۡدُودَٰتٖۚ فَمَن تَعَجَّلَ فِي يَوۡمَيۡنِ فَلَآ إِثۡمَ عَلَيۡهِۖ وَمَن تَأَخَّرَ فَلَآ إِثۡمَ عَلَيۡهِۚ لِمَنِ ٱتَّقَىٰۗ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّكُمۡ إِلَيۡهِ تُحۡشَرُونَ ٢٠٣ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُعۡجِبُكَ قَوۡلُهُۥ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَيُشۡهِدُ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا فِي قَلۡبِهِۦ وَهُوَ أَلَدُّ ٱلۡخِصَامِ ٢٠٤ وَإِذَا تَوَلَّىٰ سَعَىٰ فِي ٱلۡأَرۡضِ لِيُفۡسِدَ فِيهَا وَيُهۡلِكَ ٱلۡحَرۡثَ وَٱلنَّسۡلَۚ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلۡفَسَادَ ٢٠٥ وَإِذَا قِيلَ لَهُ ٱتَّقِ ٱللَّهَ أَخَذَتۡهُ ٱلۡعِزَّةُ بِٱلۡإِثۡمِۚ فَحَسۡبُهُۥ جَهَنَّمُۚ وَلَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ٢٠٦ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَشۡرِي نَفۡسَهُ ٱبۡتِغَآءَ مَرۡضَاتِ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ رَءُوفُۢ بِٱلۡعِبَادِ ٢٠٧

203. Kuma ku ambaci Allah a cikin wasu kwanaki ƙididdigaggu. To duk wanda ya yi gaggawar (barin Mina) cikin kwana biyu, to babu laifi a gare shi; wanda kuwa ya yi jinkiri, to babu laifi a gare shi, (amma dukkansu) ga wanda ya yi taƙawa. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani cewa, zuwa gare Shi za a tattara ku.

204. Kuma daga cikin mutane akwai wanda zancensa yake burge ka a rayuwar duniya, kuma yana shaidar da Allah ga abin da yake cikin zuciyarsa, alhali kuwa shi mai tsananin husuma ne.

205. Kuma idan ya juya baya, zai yi ta yawo a cikin ƙasa don ya yi ɓarna a cikinta, kuma ya lalata amfanin gona da dabbobi. Allah kuwa ba ya son ɓarna.

206. Idan kuma aka ce masa: “Ka kiyaye dokokin Allah” sai girman kai ya kama shi saboda saɓo. To Jahannama ta ishe shi (makwanci), kuma lalle tir da wannan makwanci.

207. Kuma daga cikin mutane akwai wanda yake sayar da kansa don neman yardar Allah. Allah kuwa Mai yawan tausayi ne ga bayi.

A waɗannan ayoyi bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin halin muminai masu yawan ambaton Allah a ko da yaushe da kuma waɗanda babu Allah a cikin lamuransu sai duniya kaɗai, sai kuma Allah ya zo da bayanin wani rukuni na mutane waɗanda maganganunsu suke ba ka sha’awa saboda fasaharsu da yadda suke sarrafa zance, musamman cikin abin da ya shafi sha’anin duniya ban da na lahira, ko kuma idan suna magana a kan taimaka wa Musulunci da Musulmai da son Manzon Allah (ﷺ), sai ka ji kamar da gaske, sai dai magana ce kawai ta fatar baki ba ta je har zuci ba. Za ka ga ɗayansu ma wani lokaci kwalliyar maganar ma ita kaɗai ba ta ishe shi ba sai ya haɗa da ƙarfafa ta da cewa, ai Allah ma ya san abin da yake faɗa ɗin nan gaskiya ce, alhalin ya san shi maƙaryaci ne mai tsananin jayayya da husuma. Idan ya fita ya bar majalisin Annabi (ﷺ) sai ya fara nuna haƙiƙanin halayensa marasa kyau da muguwar aƙidar zuciyarsa ya yi ta ƙoƙari da kazar-kazar wajen yaɗa ɓarna a doron ƙasa, ta hanyar yaɗa kafirci da munafinci da zalunci da ayyukan ta’addanci kamar fashi da makami da tsorata bayin Allah da lalata shuke-shuke da kashe dabbobi da sauran abin da rayuwa ba za ta tafi ba sai da su. Idan ya samu ya ci nasara shi ke nan ya karya tsarin rayuwa gaba ɗaya ke nan; wannan kuma da ma shi ne burinsa. Kamar kuma yadda idan ya yaɗa ɓarna ta kafirci da saɓon Allah da zalunci a ƙasa hakan zai yi sanadiyyar Allah ya hana ruwan sama, sai a shiga fari shuka ta lalace, dabbobi ma su yi ta mutuwa. Wannan kuwa shi ne sakamakon irin aikinsa, domin Allah ba ya son ɓarna, don haka ba ya son maɓarnata ko da kuwa maganganunsu na ba wa mutane sha’awa.
Mutum munafiki irin wannan duk lokacin da masu wa’azi suka yi masa wa’azi, suka neme shi da ya ji tsoron Allah, ya bar irin waɗannan miyagun laifuka da yake yi, to maimakon ya ji nasiharsu ya ɗauka, sai kawai ya kama nuna musu girman kai, laifinsa ya fi ƙarfinsa a madadin ya daina sai ma dai ya ƙara ci

gaba, to irin wannan mutum ba wani sakamako da ya dace da shi sai wutar Jahannama, ita ce za a yi masa shimfiɗa da ita ranar alƙiyama. Tir da irin wannan shimfiɗa.
A ɓangare guda kuma akwai wasu mutane waɗanda su kuma suna sayar da rayukansu ga Allah domin su sami yardarsa, Allah kuma mai tausayi ne ga bayinsa, masu irin wannan hali nagari, shi ya sa ya hore musu shiriyarsu da kimsa musu imani a zukatansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ga duk Musulmi su rungumi addinin Musulunci gaba ɗayansa, su saka shi cikin duk al'amuransu na aƙida da ibada da mu'amala da tsarin tattalin arzuƙi da tsarin shugabanci da tarbiyya da ilimi da duk wani rukuni na rayuwarsu.

2. Allah ba ya kama mai laifi da laifinsa har sai ya tsayar masa da hujja bayyananniya.

3. Tabbatar wa da Allah sifar "zuwa" ranar gobe ƙiyama, kamar yadda ta dace da Zatinsa mafi ɗaukaka.

4. Zarmewa wajen son duniya da mantawa da sha'anin lahira siffa ce ta kafirai.

5. Har ko da yaushe kafirai ba za su gushe ba suna yi wa muminai kallon izgili saboda addininsu.

6. Yi wa masu riƙo da addini izgili wata sifa ce daga cikin sifofin kafirai.

7. Matsayi da daraja ta gaskiya ita ce wadda mutum zai samu a lahira, ba wadda zai samu a nan duniya saboda abin duniya ba.

8. Asalin 'yan'adam sun rayu ne da farko a kan addini na kaɗaita Allah da bauta, wato Musulunci, daga baya ne Shaiɗan ya halakar da su ya mayar da su suna bautar wanin Allah.

9. Yana daga cikin manyan ni'imomin da Allah ya yi wa bayinsa bai ƙyale su su binciko shiriya da hankulansu kawai ba, a'a, ya aiko musu da annabawa sannan ya saukar musu da littattafai.

10. Wajibi ne a kan Musulmi idan an yi saɓani a kan wani lamari na addini ya roƙi Allah ya nuna masa inda gaskiya take domin ya bi ta, kada ya ce duk lalube ake a duhu, don haka ya yi zaɓi sonka ya bi son zuciyarsa.

11. Riƙo da addini yana buƙatar haƙuri da juriya a kan jarraba ta Allah. Duk wani tsanani kuma yana tare da sauƙi.

Suratul Baƙara (208-214)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱدۡخُلُواْ فِي ٱلسِّلۡمِ كَآفَّةٗ وَلَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ٢٠٨ فَإِن زَلَلۡتُم مِّنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡكُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٢٠٩ هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن يَأۡتِيَهُمُ ٱللَّهُ فِي ظُلَلٖ مِّنَ ٱلۡغَمَامِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَقُضِيَ ٱلۡأَمۡرُۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ ٢١٠ سَلۡ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ كَمۡ ءَاتَيۡنَٰهُم مِّنۡ ءَايَةم بَيِّنَةٖۗ وَمَن يُبَدِّلۡ نِعۡمَةَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡهُ فَإِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٢١١ زُيِّنَ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا وَيَسۡخَرُونَ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْۘ وَٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ فَوۡقَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ وَٱللَّهُ يَرۡزُقُ مَن يَشَآءُ بِغَيۡرِ حِسَابٖ ٢١٢ كَانَ ٱلنَّاسُ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ فَبَعَثَ ٱللَّهُ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ وَأَنزَلَ مَعَهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ لِيَحۡكُمَ بَيۡنَ ٱلنَّاسِ فِيمَا ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِۚ وَمَا

ٱخۡتَلَفَ فِيهِ إِلَّا ٱلَّذِينَ أُوتُوهُ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۖ فَهَدَى ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لِمَا ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِ مِنَ ٱلۡحَقِّ بِإِذۡنِهِۦۗ وَٱللَّهُ يَهۡدِي مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٍ ٢١٣ أَمۡ حَسِبۡتُمۡ أَن تَدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ وَلَمَّا يَأۡتِكُم مَّثَلُ ٱلَّذِينَ خَلَوۡاْ مِن قَبۡلِكُمۖ مَّسَّتۡهُمُ ٱلۡبَأۡسَآءُ وَٱلضَّرَّآءُ وَزُلۡزِلُواْ حَتَّىٰ يَقُولَ ٱلرَّسُولُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ مَتَىٰ نَصۡرُ ٱللَّهِۗ أَلَآ إِنَّ نَصۡرَ ٱللَّهِ قَرِيبٞ ٢١٤

208. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku shiga cikin addinin Musulunci gaba ɗaya, kuma kar ku bi hanyoyin Shaiɗan. Lalle shi maƙiyi ne a gare ku, mai bayyana (ƙiyayya).

209. To idan kuka zame bayan hujjoji bayyanannu sun zo muku, to ku sani cewa, lalle Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.

210. Shin ko akwai abin da suke jira ne, in ban da Allah Ya zo musu a cikin waɗansu inuwoyi na gizagizai da mala'iku, sai a zartar da al'amari? Kuma zuwa ga Allah ne ake mayar da al'amura.

211. Ka tambayi Banu Isra'ila, sau nawa Muka ba su wata aya bayyananniya? Kuma duk wanda ya musanya ni'imar Allah bayan ta zo masa, to lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne.

212. An ƙawata wa kafirai rayuwar duniya, kuma suna yin izgili ga waɗanda suka yi imani. Waɗanda kuwa suka yi taƙawa su ne a samansu a ranar alƙiyama. Kuma Allah Yana arzurta wanda ya ga dama, ba tare da lissafi ba.

213. Mutane sun kasance al'umma guda ɗaya, sai Allah Ya aiko da annabawa, suna masu albishir, kuma masu gargaɗi, kuma Ya saukar da littafi tare da su da gaskiya, don ya yi hukunci tsakanin mutane cikin abin da suka yi saɓani a kansa. Kuma ba wasu ne suka yi saɓani a kansa ba sai waɗanda aka ba wa shi, bayan hujjoji bayyanannu sun zo musu, don zalunci a tsakaninsu; sai Allah Ya shiryar da waɗanda suka yi imani ga abin da (mutane) suka yi saɓani cikinsa na gaskiya da izininsa. Kuma Allah Yana shiryar da wanda Ya ga dama zuwa ga tafarki madaidaici.

214. Shin kun yi tsammanin za ku shiga Aljanna ne, alhalin misalin irin abin da ya shafi waɗanda suka shuɗe gabaninku bai zo muku ba? Tsananin talauci da cuta sun shafe su; kuma an girgiza su sosai, har Manzo da waɗanda suka yi imani tare da shi suka riƙa cewa: “Yaushe ne nasarar Allah za ta zo?” Ku saurara, lalle nasarar Allah a kusa take.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffofin rukunai daban-daban na mutane, kama daga ‘yan duniya waɗanda babu abin da suka sa a gaba sai neman ta ido rufe zuwa ga munafuƙai masu nuna imani da ƙaunar Allah a baki, amma in sun koma gefe ban da ɓarna babu abin da suka sa a gaba, sai kuma muminai na gaskiya masu tsoron Allah da neman yardarsa. A waɗannan ayoyi kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo muminai gaba ɗaya yana umartar su da shiga Musulunci gaba ɗaya, wato su yi aiki da duk shari’un Musulunci. Yana yi musu gargaɗi kada su bi tafarkin Shaiɗan domin shi maƙiyansu ne na ɓoye da sarari, don haka yi masa biyayya yana nufin aukawarsu cikin halaka; idan suka kuskura har suka aikata ayyukan da suka saɓawa koyarwar Musulunci da gangan, to su sani cewa, babu wani abu da zai gagari Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) don haka shi mai iya hukunta su ne, domin ƙarfinsa ya fi na kowa da komai, wanda duk ya cancanci azaba Allah zai yi masa azabar da ta dace da shi domin ayyukansa gaba ɗaya suna tare da hikima,
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana inkarinsa ga waɗanda suka kauce wa hanyar gaskiya bayan sun ga hujjoji bayyanannu. Wannan abu da suka yi yana nuna kawai suna jiran lokacin halaka su

ne ya zo, wato lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai zo ranar gobe ƙiyama tare da mala'iku, domin ya zartar musu hukunci na adalci, ya yi sakayya ga waɗanda suka kafirta a nan duniya; wannan kuwa ita ce halaka ta haƙiƙa.
Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Allah zai tattara mutanen farko da na ƙarshe a ranar gobe ƙiyama har tsawon shekara arba'in idanuwansu bubbuɗe suna kallon sama, suna jiran a yanke musu hukunci, sai Allah ya sauko daga Al'arshi zuwa Kursiyyi cikin inuwoyi na girgije" [Dubi: Aɗɗabarani, *Al-Mu'jamul Kabir* #9763, Ad-Daraƙuɗuni, *Ru'yatullah*i #163, Ibn Nasr, *Ta'azimu Kadris Sala*t #278]. Azzahabi da Ibnul Kayyim da Albani sun tabbatar da wannan hadisin [Dubi: *Kitabul Arsh*, Shafi na 76, *Hadil Arwah*, Shafi na 262, *Sahihut-Targib* #3591].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa (ﷺ) da ya tambayi Yahudawa game da abin da Allah ya ba su na hujjoji bayyanannu da mu'ujizozi masu yawa waɗanda suka tabbatar da gaskiyar annabawa da manzanni da Allah ya aiko musu, amma duk da haka sai suka riƙa ƙaryata wasu annabawan, suka riƙa kafirce musu suna juya wa waɗannan hujjoji da ayoyi baya. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin narko da uƙuba ga duk wanda ya zaɓi kafirci a maimakon ni'imar Musulunci bayan ya zo masa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cewa, an ƙawata ni'imomin duniya a idanuwan kafirai da zukatansu, sun kuma yarda da ita sun fifita ta a kan ni'imar lahira, suna kuma yi wa muminai izgili wai don ganin su ba su ɗauki ƙyale-ƙyalen duniya a bakin komai ba. Sun manta cewa, fifiko na haƙiƙa da ɗaukakar daraja ta gaskiya ita ce ta ranar lahira. Ai waɗanda suka yi imani suka yi ayyuka nagari a nan duniya su za su zama a sama da duk wani kafiri, domin Allah zai ba su gidan Aljanna, ya ba su duk abin da suke sha'awa a cikinta, yayin da su kuma kafirai 'yan ƙyale-ƙyale za su kasance a gidan wutar Jahannama cikin azaba marar ƙaƙƙautawa kuma ta har abada. Allah yana ba wa muminai falalarsa a Aljanna ba tare da lissafi ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, mutane tun daga zamanin Annabi Adamu suke bautar Allah a kan addini guda ɗaya, shi ne Musulunci, haka suka rayu tsawon ƙarni goma a jere. Daga bisani sai saɓanin addini ya shigo su har ta kai sun koma bautar gumaka, daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko annabawansa suka riƙa hana mutane bautar wanin Allah, suna umartar su da bautar Allah shi kaɗai, suna yin albishir da ni'imar Aljanna ga duk wanda ya bi su, suna gargaɗi da wuta ga duk wanda ya saba musu.
Na farkon waɗannan annabawa da Allah ya aika shi ne Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya saukar wa waɗannan annabawan da littattafai waɗanda suka ƙunshi labarai na gaskiya da dokoki na adalci don su yi hukunci da su a tsakanin mutanensu game da duk wani abu da suke jayayya a kansa, domin gaskiya ta bayyana a san ta, ƙarya ma ta fito a gane ta, a gane daidai a gane kuskure; daga nan hujjar Allah ta tsayu a kan bayinsa. To amma duk da cewa littattafan da Allah ya saukar, ya saukar da su ne don kan jama'a ya haɗu a kan aiki da gaskiyar da suka ƙunsa, to sai ga shi wasu sun saba wa muradin Ubangiji, suka sassaba a kan littattafan su kansu, wasu suka yarda da su suka yi imani da gaskiyar da take cikinsu, da yawa kuma suka ƙi yarda, suka ma ƙaryata gaskiyar da ta zo cikinsu, bayan dukansu sun samu hujjoji masu yanke shakku a kan ingancinsu. Kuma babban abin da ya jawo musu wannan saɓani shi ne samun wasunsu suna zaluntar wasu; to sai Allah ya shiryar da muminai zuwa ga bin miƙaƙƙiyar hanya, ya datar da su suka rungumi gaskiya suka riƙe ta ƙam-ƙam. Haka Allah yake shiryar da duk wanda ya ga dama cikin bayinsa ya nuna masa gaskiya ya ba shi ikon bin ta.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin irin yadda al'ummomin baya suka sassaba wa annabawansu, suka saki gaskiya suka kama ƙarya, ya kuma shiryar da muminai bin tafarki madaidici, to sai kuma ya bayyana musu cewa, bin wannan hanya miƙaƙƙiya yana tattare da wasu wahalhalu da jarraba iri-iri, don haka al'amarin yana buƙatar haƙuri da juriya. Allah ya faɗa wa muminai cewa, kada su yi tsammanin cewa, wannan hanya mai sauƙi ce, a'a cike take da matsaloli da wahalhalu iri-iri. Al'ummomin da suka gabata sun ɗanɗani tsananin talauci da rashi da cutuƙuka iri-iri; maƙiyansu suka tayar musu da hankali matuƙa gaya, har sai da lamarin ya kai manzannin da muminai suna tambayar

juna: Yaushe ne taimakon Allah zai zo, domin su samu su fita daga wahalhalun da suke ciki? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, nasarar Allah tana nan tafe kusa ba daɗewa, domin ko mene ne ya yi tsanani to sauƙi yana nan tare da shi, kamar yadda Allah ya ambata a *Suratus Sharhi*, aya ta 5-6.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ga bawa ya sallama wa umarnin Allah, ya karɓi dokarsa da yarda da amincewa. Sau da yawa mutum yakan ƙi abu tare da cewa a cikinsa akwai tarin alheri wanda bai san da shi ba. Haka kuma sau da yawa mutum yakan ƙwallafa ransa ga wani abu alhalin a cikinsa akwai sharri mai yawa wanda bai san da shi ba.

2. Bai halatta ga wani mutum ya yanke hukuncin cewa an karɓi aikinsa na alheri da ya yi ba, a'a, ya zamana yana tsakanin kyakkyawan fata da kuma tsoro; wannan ita ce siffar bayin Allah na ƙwarai.

3. Musulunci ya zo da samar da abin da yake maslaha ce da kawar da duk abin da yake ɓarna.

4. Aunawa tsakanin maslaha da ɓarna cikin duk wani al'amari babbar manufa ce daga manufofin shari'a.

5. Aikin tallafa wa juna a cikin al'umma wani jigo ne mai muhimmanci ga rayuwar al'ummar Musulmi. Dole ne al'ummar Musulmi su tallafa wa masu rauni a cikinsu, kuma waɗanda suka fi cancantar a tallafa wa su ne marayu, domin ƙanƙantarsu da rashin iyaye maza masu kula da su.

6. Himmar sahabbai a kan neman ilimi, shi ya sa suka yawaita yin tambayoyi game da addininsu da rayuwarsu.

7. Gargaɗi ga Musulmi da kada su saki jiki da kafirai domin ba za su taɓa son su da alheri ba sai dai su cutar da su ta fuskar addininsu.

Suratul Baƙara (215-220)

يَسْـَٔلُونَكَ مَاذَا يُنفِقُونَۖ قُلْ مَآ أَنفَقْتُم مِّنْ خَيْرٍ فَلِلْوَٰلِدَيْنِ وَٱلْأَقْرَبِينَ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِۗ وَمَا تَفْعَلُواْ مِنْ خَيْرٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ بِهِۦ عَلِيمٌ ﴿٢١٥﴾ كُتِبَ عَلَيْكُمُ ٱلْقِتَالُ وَهُوَ كُرْهٌ لَّكُمْۖ وَعَسَىٰٓ أَن تَكْرَهُواْ شَيْـًٔا وَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْۖ وَعَسَىٰٓ أَن تُحِبُّواْ شَيْـًٔا وَهُوَ شَرٌّ لَّكُمْۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ﴿٢١٦﴾ يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلشَّهْرِ ٱلْحَرَامِ قِتَالٍ فِيهِۖ قُلْ قِتَالٌ فِيهِ كَبِيرٌۚ وَصَدٌّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَكُفْرٌۢ بِهِۦ وَٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ وَإِخْرَاجُ أَهْلِهِۦ مِنْهُ أَكْبَرُ عِندَ ٱللَّهِۚ وَٱلْفِتْنَةُ أَكْبَرُ مِنَ ٱلْقَتْلِۗ وَلَا يَزَالُونَ يُقَٰتِلُونَكُمْ حَتَّىٰ يَرُدُّوكُمْ عَن دِينِكُمْ إِنِ ٱسْتَطَٰعُواْۚ وَمَن يَرْتَدِدْ مِنكُمْ عَن دِينِهِۦ فَيَمُتْ وَهُوَ كَافِرٌ فَأُوْلَٰٓئِكَ حَبِطَتْ أَعْمَٰلُهُمْ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ﴿٢١٧﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ هَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ يَرْجُونَ رَحْمَتَ ٱللَّهِۚ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ﴿٢١٨﴾ * يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْخَمْرِ وَٱلْمَيْسِرِۖ قُلْ فِيهِمَآ إِثْمٌ كَبِيرٌ وَمَنَٰفِعُ لِلنَّاسِ وَإِثْمُهُمَآ أَكْبَرُ مِن نَّفْعِهِمَاۗ وَيَسْـَٔلُونَكَ مَاذَا يُنفِقُونَۖ قُلِ ٱلْعَفْوَۗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلْأَيَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَتَفَكَّرُونَ ﴿٢١٩﴾ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِۗ وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْيَتَٰمَىٰۖ قُلْ إِصْلَاحٌ لَّهُمْ خَيْرٌۖ وَإِن تُخَالِطُوهُمْ فَإِخْوَٰنُكُمْۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ ٱلْمُفْسِدَ مِنَ ٱلْمُصْلِحِۚ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ لَأَعْنَتَكُمْۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٢٢٠﴾

215. Suna tambayar ka, me za su ciyar ne? Ka ce: “Duk abin da za ku ciyar na alheri, to ga mahaifa da dangi mafiya kusanci da marayu da miskinai da matafiyi. Kuma duk abin da kuka aikata na alheri, to lalle Allah Yana sane da shi.”

216. An wajabta muku yaƙi (ku muminai), ga shi kuwa kuna ƙin sa, kuma zai iya yiwuwa ku ƙi wani abu alhalin shi alheri ne a gare ku, kuma zai iya yiwuwa ku so wani abu alhalin shi sharri ne a gare ku. Kuma Allah Shi yake da sani, ku ba ku sani ba.

217. Suna tambayar ka game da wata mai alfarma, yin yaƙi a cikinsa. Ka ce: “Yaƙi a cikinsa, babban laifi ne, amma hana (mutane) bin tafarkin Allah da kafirce masa da kuma (hana mutane shiga) Masallaci mai alfarma da fitar da mutanensa daga gare shi, su ne mafi girman laifi a wajen Allah. Kuma (laifin) fitina ya fi na kisa girma.” Kuma (kafirai) ba za su gushe ba suna yaƙar ku, har sai sun raba ku da addininku, idan da za su sami dama. Kuma duk wanda ya yi ridda daga cikinku, ya bar addininsa, kuma ya mutu yana kafiri, to waɗannan ayyukansu sun lalace a duniya da lahira, kuma waɗannan su ne ma'abota wuta, suna masu dawwama a cikinta.

218. Lalle waɗanda suka yi imani da kuma waɗanda suka yi hijira, kuma suka yi jihadi don Allah, waɗannan su ne suke fatan rahamar Allah; Allah kuwa Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.

219. Suna tambayar ka game da giya da caca. Ka ce: “A cikin lamarinsu akwai zunubi mai girma da kuma waɗansu amfanunnuka ga mutane. Amma zunubinsu ya fi amfaninsu girma” Kuma suna tambayar ka, me za su ciyar? Ka ce: “Abin da ya daɗu a kan buƙatunku.” Kamar haka ne Allah Yake muku bayanin ayoyi don ku yi tunani.

220. Game da lamarin duniya da lahira. Kuma suna tambayar ka game da marayu. Ka ce : “Inganta musu dukiyarsu shi ne mafi alheri, kuma in kuka haɗa cimakarku da tasu, to ai 'yan’uwanku ne. Amma fa Allah Ya san mai son yin ɓarna daga wanda yake son yin gyara. Kuma da Allah Ya ga dama da Ya ƙuntata muku. Lalle Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda Musulmin farko (sahabbai) suka riƙa yin tambayoyi game da sha’anin addininsu da rayuwarsu domin su dace da aƙidarsu ta Musulunci. Kamar yadda ayoyin suka yi bayanin wasu tambayoyi da suka riƙa tasowa saboda surutai da soke-soke na Yahudawa da munafuƙai da mushrikai a kan wasu al’amura, wannan ya sa Musulmi suka riƙa yin tambayoyi a kai domin su sami yaƙini game da waɗannan al’amura.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, sahabbansa suna yi masa tambaya game da abin da za su ciyar, mene ne shi? Kuma ya ya gwargwadon yawansa? Kuma ta yaya za su fitar da shi? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya amsa musu cewa, abin da duk za su ciyar ba a ƙayyade shi da wani jinsin dukiya ko wani gwargwado na musamman ba; duk abin da Allah ya hore wa mutum yana iya sadaka da shi, kaɗan ne ko mai yawa. Amma kuma waɗanda ya fi cancanta ya fara da su su ne waɗanda suka fi kusanci da shi, wato iyalansa sannan sauran danginsa gwargwadon kusancin kowane, sannan waɗanda suka fi buƙata cikin al’umma, kamar marayu sannan mabuƙata waɗanda ba su da abin da zai riƙe su, sannan matafiyi wanda guzurinsa ya ƙare, a taimaka masa da abin da zai maida shi garinsu. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk abin da za su yi na kyautatawa ko na alheri to ba zai ɓoyu ba a wajen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sane da shi kuma zai yi sakayya gwaggwaɓa a kansa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin farlanta wa bayinsa muminai fita yaƙi, duk da cewa ya san ba sa son hakan, saboda abin da yaƙi ya gada na salwantar rayuka da dukiya da lafiya da abin da yake tattare da shi na tsoro da fargaba. To amma idan an dubi abin ta wani ɓangare akwai alheri mai

yawa a cikinsa, domin yana tare da murƙushe abokan gaba da samun nasara a kansu ko mutuwar shahada ga wanda Allah ya ƙaddara mutuwarsa a yaƙin, da kare addini da mutunci da ƙasa da koyar da maƙiya darasi, da sauran al'amura na maslaha waɗanda sun zarce zama ba tare da fita yaƙin ba. Haka kuma duk inda ayyukan alheri suke suna tattare da abin da zukata ba sa so, to amma alherin cikinsu mai yawa ne. Hakanan ayyukan sharri suna tattare da abin da zukata ke ƙauna, amma sharrinsu mai yawa ne. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne kawai ya san abin da zai amfanar da al'umma da kuma marar amfani gare su. Don haka sai su bi umarninsa su kuma yi aiki da shari'arsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, sahabbansa suna tambayar sa a kan hukuncin yaƙi a cikin watanni masu alfarma. Sai kuma ya faɗa masa amsar da zai ba su, da cewa, yaƙi a waɗannan watanni babban lamari ne, sai dai kuma abin da mushrikai suke yi na hana mutane shiga addinin Allah da kafirce wa Allah da hana muminai zuwa Ɗakin Allah mai alfarma da ke Makka da korar muminai da suke wannan gari na Makka; waɗannan ayyuka da suke yi sun fi yaƙi a watanni masu alfarma girman zunubi a wurin Allah. Duk waɗannan ayyuka na mushrikai fitina ce wadda ta fi tsananin muni a wurin Allah fiye da kisan da Musulmi suka yi a cikin wata mai alfarma.

Dalilin saukar wannan aya kuwa shi ne, wata rana Annabi (ﷺ) ya aika da wata ƙaramar runduna ƙarƙashin jagorancin Abdullahi ɗan Jahshi, sai suka gamu da wani mushriki ana ce masa Ibnul Hadhrami, sai suka kashe shi, ba su san cewa a watan Rajab suke ba. Sai mushrikai suka riƙa faɗa wa Musulmai cewa: "Kun yi kisa a cikin wata mai alfarma". Sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Suna tambayar ka game da wata mai alfarma, yin yaƙi a cikinsa." Daga nan sai kuma wasu suka riƙa cewa: "Ko ba su da laifi, to amma kuma ba su da lada." Sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Lalle waɗanda suka yi imani da kuma waɗanda suka yi hijira kuma suka yi jihadi don yaɗa kalmar Allah, waɗannan su ne suke fatar samun rahamar Allah; Allah kuwa mai yawan gafara ne mai yawan jin ƙai." [An-Nasa'i *As-Sunan Al-Kubra* #8803, Abu Ya'ala #1534, At-Tabarani #1670].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Musulmi irin mummunar ƙiyayyar kafirai a gare su saboda addininsu, kuma ba za su gushe ba suna yaƙar su ta hanyoyi daban-daban domin cim ma manufarsu wadda ita ce su raba su da addininsu su mayar da su kafirai irinsu idan har za su samu wannan damar. To amma har abada ba za su samu ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk Musulmin da ya yi ridda ya bar addininsa har ya mutu bai tuba ba, to duk ayyukan ibada da na alheri da ya taɓa yi sun rushe, ba wani aikin da zai samu ladansa a wurin Allah, kuma ya zama ɗan wuta mai dawwama a cikinta har abada. To amma waɗanda suka miƙa wuya ga gaskiya, suka yi imani, suka yi hijira daga garuruwansu don tsira da addininsu, sannan suka yaƙi maƙiya Allah don taimakon addininsu da ɗaukaka kalmar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka); to waɗannan su ne suke sa ran samun rahamar Allah da Karramawarsa, kuma lalle Allah zai girmama su ya ba su ladan da suke fatan su samu a wurinsa, saboda shi Allah mai yafe zunubbai ne, mai rahama ne ga bayinsa, yana musu gwaggwaɓar sakayya a kan ayyukansu, a duniya da lahira.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, sahabbansa suna tambayar sa hukuncin shan kayan sa maye da hukuncin caca; sai ya umarce shi da ya ba su amsa da cewa, game da ta'ammuli da kayan maye da caca akwai ɓarna mai yawan gaske da laifuka masu girma; saboda abin da suke haifarwa a tsakanin jama'a na gaba da ƙiyayya da hana ambaton Allah da tsayar da salla. Sannan kuma ta gefe guda akwai amfani ga mutane masu ta'ammuli da su, kamar abin da giya take haifar wa da mashayinta na manta duk wata damuwarsa ta rayuwa ko dukiyar da masu caca suke samu ta hanyarta. Sai dai idan an kwatanta tsakanin amfaninsu da ɓarnar da suke haifarwa da irin zunuban da suke tattare da su babu shakka ɓarnar ta zarce amfanin nesa ba kusa ba.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, sahabbai suna yi masa tambaya game da abin da za su bayar sadaka daga cikin dukiyoyinsu, sai ya umarce shi da ya amsa musu da cewa, su ciyar da abin da ya yi saura a kan buƙatunsu na yau da gobe.

Hakanan ya faɗa masa cewa, suna yi masa tambaya game da dukiyar marayu da take zama a hannuwansu, yaya ya kamata su mu'amalance ta don kada su faɗa cikin matsala. Sai ya umarce shi da ya

ba su amsa da cewa, babban abin buƙata dangane da dukiyar maraya shi ne kulawa da ita da haɓaka ta. To idan sun yi hakan ba tare da sun karɓi komai na lada daga wurinsu ba, wannan suna da lada mai girma a wurin Allah. Idan kuma sun ɗauki wani abu na ladan wahalarsu wajen juya dukiyar can, kamar su haɗa cimarsu tare da ta marayu ko su riƙa cirar wani abu daga ribar dukiyar gwargwadon wahalarsu, to wannan ma ya halatta, amma da sharaɗin kada su cuci marayun, domin su nan 'yan'uwansu ne na addini, ɗan'uwa kuwa yana iya haɗa cimarsa da ta ɗan'uwansa babu wata damuwa ga yin haka. Amma duk da haka kada su manta da cewa, Allah yana nan yana sa ido a kan duk abin da suke yi; wanda duk yake da mummunan nufin lalata dukiyar maraya da cinye masa ita, Allah yana sane da shi, hakanan wanda yake da kyakkyawar niyyar taimaka wa maraya da gyara masa dukiyarsa shi ma Allah yana sane da shi, kuma zai saka wa kowa gwargwadon aikinsa da niyyarsa. Wannan hukunci da wannan sauƙi daga Allah ne domin ya sauƙaƙa wa bayinsa ya kawar musu da duk wani abu da zai ƙuntata musu. Da Allah ya ga dama da sai ya jefa su cikin ƙunci da wahala domin Allah mabuwayi ne babu abin da zai gagare shi, amma kuma mai hikima ne yana sanya komai a muhallinsa da ya dace da shi.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "Kada ku kusanci dukiyar maraya sai ta hanyar da take mafi kyau", da kuma faɗarsa: "Lalle waɗanda suke cin dukiyar marayu bisa zalunci…." sai duk wani mai maraya a ƙarƙashinsa ya koma gida, ya raba abincinsa da abin shansa da na maraya, idan ya ci abinci ya rage sai ya ajiye masa har sai ya cinye ko ya lalace. To wannan al'amari ya dami sahabbai, sai suka sanar da Annabi (ﷺ) halin da suke ciki, sai Allah ya saukar da wannan ayar: (kuma suna tambayar ka game da marayu. Ka ce: "Inganta musu dukiyarsu shi ne mafi alheri, kuma in kuka haɗa cimarku da tasu to ai 'yan'uwanku ne." Daga lokacin sai suka dinga haɗa abincinsu da abin shansu da nasu). [Abu Dawud #2871, da Ahmad #3002].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mumini duk yadda yake, ya fi kafiri daraja. Don haka kada mutum ya ruɗu da ƙarfin kafiri ko iya maganarsa ko wani abu mai kama da haka.

2. Kada kunya ta hana tambaya a kan sha'anin addini.

3. Allah yana son bawa ya haɗa tsarki na zahiri da tsarki na baɗini. Shi ya sa ya haɗa tsakanin tuba daga zunubbai (tsarki na baɗini), da kuma tsarki na najasa ko ƙazanta (tsarki na zahiri).

4. Allah ya siffantu da siffar 'so'. Yana son bayinsa masu tuba, yana son masu tsarki.

5. Muhimmancin kula da matan aure. Shi ya sa Allah ya ambace su da 'gonakinku'.

6. Haramcin saduwa da mace ta dubura.

7. Kwaɗaitarwa a kan ayyukan alheri, saboda haka Allah ya nuna kada rantsuwa ta hana mutum aikin alheri. To ina kuma idan bai riga ya yi rantsuwar ba?

8. Falarar yin sulhu tsakanin mutane masu husuma. Yin haka yana daga cikin manya-manyan ayyukan alheri.

Suratul Baƙara (221-224)

وَلَا تَنكِحُواْ ٱلۡمُشۡرِكَٰتِ حَتَّىٰ يُؤۡمِنَّۚ وَلَأَمَةٞ مُّؤۡمِنَةٌ خَيۡرٞ مِّن مُّشۡرِكَةٖ وَلَوۡ أَعۡجَبَتۡكُمۡۗ وَلَا تُنكِحُواْ ٱلۡمُشۡرِكِينَ حَتَّىٰ يُؤۡمِنُواْۚ وَلَعَبۡدٞ مُّؤۡمِنٌ خَيۡرٞ مِّن مُّشۡرِكٖ وَلَوۡ أَعۡجَبَكُمۡۗ أُوْلَٰٓئِكَ يَدۡعُونَ إِلَى ٱلنَّارِۖ وَٱللَّهُ يَدۡعُوٓاْ إِلَى ٱلۡجَنَّةِ وَٱلۡمَغۡفِرَةِ بِإِذۡنِهِۦۖ وَيُبَيِّنُ ءَايَٰتِهِۦ لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ٢٢١ وَيَسۡـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلۡمَحِيضِۖ قُلۡ هُوَ أَذٗى فَٱعۡتَزِلُواْ ٱلنِّسَآءَ فِي ٱلۡمَحِيضِ وَلَا تَقۡرَبُوهُنَّ حَتَّىٰ يَطۡهُرۡنَۖ فَإِذَا تَطَهَّرۡنَ فَأۡتُوهُنَّ مِنۡ حَيۡثُ أَمَرَكُمُ ٱللَّهُۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلتَّوَّٰبِينَ وَيُحِبُّ ٱلۡمُتَطَهِّرِينَ ٢٢٢ نِسَآؤُكُمۡ حَرۡثٞ لَّكُمۡ فَأۡتُواْ حَرۡثَكُمۡ أَنَّىٰ شِئۡتُمۡۖ وَقَدِّمُواْ لِأَنفُسِكُمۡۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّكُم مُّلَٰقُوهُۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٢٢٣ وَلَا تَجۡعَلُواْ ٱللَّهَ عُرۡضَةٗ لِّأَيۡمَٰنِكُمۡ أَن تَبَرُّواْ وَتَتَّقُواْ وَتُصۡلِحُواْ بَيۡنَ ٱلنَّاسِۚ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٢٢٤

221. Kuma kada ku auri mata mushirikai har sai sun yi imani, kuma lalle baiwa mumina ta fi 'ya mushirika alheri, ko da (mushirikar) ta burge ku. Kuma kada ku aurar wa mushirikai har sai sun yi imani; kuma lalle bawa mumini ya fi (ɗa) mushiriki alheri, ko da ya burge ku. Su waɗancan (kafirai), suna kira ne zuwa ga wuta, Allah kuwa Yana kira ne zuwa ga Aljanna da gafara da izininsa, kuma Yana bayyana ayoyinsa ga mutane don su wa'azantu.

222. Kuma suna tambayar ka game da jinin haila. Ka ce: “Shi cuta ne, don haka ku ƙaurace wa mata a (kwanakin) haila, kuma kada ku kusance su har sai sun tsarkaka. To idan suka yi tsarki, sai ku zo musu ta inda Allah Ya umarce ku. Lalle Allah Yana son masu yawan tuba, kuma Yana son masu tsarki.”

223. Matanku gonaki ne a gare ku, don haka ku zaike wa gonakinku ta inda kuka ga dama, kuma ku gabatar wa kawunanku (laduban da shari'a ta tanadar muku). Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani cewa, lalle ku masu saduwa ne da Shi. Kuma ka yi albishir ga muminai.

224. Kuma kada ku mayar da Allah Ya zamanto kariya ga rantse-rantsenku don su hana ku aiki na ɗa'a ko na taƙawa ko na sulhu tsakanin mutane. Kuma Allah Mai ji ne, Masani.

Daga aya ta 221 har zuwa aya ta 242, wani kundi ne na tsarin zamantakewar iyali. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa wannan rukuni na rayuwar ɗan’adam muhimmancin gaske, domin ginuwarsa tana farawa ne daga gidan da ya fito. Samun mutum nagari, wanda ya san darajar rayuwarsa a bayan ƙasa da manufar halittarsa a duniya, shi ne abin da zai taimaka wajen samar da al’umma ta gari, wadda za ta raya ƙasa, ta kiyaye dokokin Allah a rayuwa. Don haka waɗannan ayoyi suka yi bayani a kan mas’alolin aure da zamantakewar aure da ila’i da saki da idda da ciyarwa da shayarwa da raino da sauran wasu al’umura masu alaka da hakan.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara bayaninsa a kan hukuncin aure tsakanin mace mushrika da mumini, ko tsakanin mumina da mushriki. Allah ya hana irin wannan aure har sai idan sun musulunta. Kuma ɗa namiji mumini ya auri mace baiwa mumina, ya fi masa alheri da ya auri mace ‘ya mushrika, wadda ba ta kaɗaita Allah, ko da kuwa tana da wani abu tare da ita da zai ja hankalinsa, kamar tsalelen kyau ko asali na nasaba ko tarin dukiya. Hakanan su ma mata muminai kada iyayensu, ko waliyyansu, su kuskura su bayar da su aure ga waɗanda suke mushirikai, matuƙar ba su shiga addinin Musulunci ba. Su ba da su aure ga bayinsu muminai, ya fi alheri wurin Allah, fiye da su ba wa ‘ya’yan mushirikai ‘ya’yansu mata, ko da kuwa su ‘ya’yan mushrikan suna da abin da zai ja hankali, kamar kyau ko asali ko dukiya ko sarauta, saboda duk wanda ba Musulmi ne ba, zai ja wanda yake tare da shi ne zuwa son duniya fiye da lahira, ya jefa shi cikin ayyukan da za su kai shi ga shiga wuta. Shi kuma Allah yana kira ne zuwa ga Aljanna, ta hanyar koyar da bayinsa shari’arsa, wadda ta ƙunshi umarni da hani, waɗanda aiki da su ne zai kai

mutum ga shiga Aljanna. Kamar yadda Allah yake kwaɗaitarwa a kan tuba da neman gafara da lizimtar ayyuka na ƙwarai, waɗanda za su zama kaffara ga zunubban bawa. Da haka ne Allah yake bayyana hujjojinsa da hukunce-hukuncensa da hikimominsa ga mutane, wala'alla hakan zai sa su tuna abin da suka manta na gaskiya, su ɗau izina, su wa'azantu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa cewa, muminai suna tambayar sa game da hukuncin mu'amalar aure tare da matansu yayin da suke jinin haila, shin za su ƙaurace musu ne gaba ɗaya ko za su kusance su ta hanyar saduwa? Sai Allah ya ce, ya faɗa musu cewa, shi jinin haila cuta ce, kuma ƙazanta ce, kada su sadu da matansu lokacin da suke al'adarsu ta haila, har sai jininsu ya ɗauke sun yi wanka, to a lokacin ne ya halatta su sadu da su ta inda Allah ya halatta musu saduwa da su, wato matancinsu. Allah ya yi bayanin wannan hukunci ne ga bayinsa saboda yana son masu tuba su tsarkake zukatansu daga laifuffuka, kuma masu tsarkake jikinsu daga duk wata najasa da wata ƙazanta.

An karɓo daga Anas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Yahudawa sun kasance idan mace a cikinsu tana haila, to ba sa cin abinci tare da ita, ba sa zama gida ɗaya da ita. Sai sahabban Annabi (ﷺ) suka yi tambaya a kan haka, sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Kuma suna tambayar ka game da jinin haila. Ka ce: 'Shi cuta ne, don haka ku ƙaurace wa mata a kwanakin haila.' Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa sahabbai: "Ku yi komai da su, amma ban da saduwa." [Muslim #302].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sanar da bayinsa cewa, matansu gonakinsu ne, a cikin mahaifarsu suke saka 'ya'yansu tun suna ɗigon maniyyi, har su girma a haife su a matsayin mutane da ikon Allah. Don haka ya halatta a gare su su sadu da matansu ta kowane ɓangare suka ga dama, matuƙar za su zo musu ta gabansu, wajen da shi ne muhallin shukar 'ya'ya a mahaifa. Sannan Allah ya umarce su da su yi tanadin ayyukan alheri waɗanda za su amfane su a gidan lahira, kuma ya umarce su da su bi dokokinsa ta hanyar aiki da umarninsa da barin duk abin da ya hana, sannan su tabbatar su sakankance cewa, makomarsu zuwa ga Allah take. Sannan ya umarci Annabinsa da ya yi albishir ga muminai na sakamako mai girma da za su samu a wurin Allah.

Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: "Yahudawa suna da'awar cewa, idan mutum ya tara da matarsa ta bayanta, wai za ta haifi ɗa mai harare-garke. Sai wannan aya ta sauka: "Matanku gonaki ne a gare ku, don haka ku je wa gonakinku ta inda kuka ga dama." [Muslim #1435].

Abun Nadhr ya ce wa Nafi'u, bararren bawan Abdullahi ɗan Umar: "Ana ta faɗin cewa, kana cewa Ibn Umar ya ba da fatawar halaccin saduwa da mata ta duburarsu." Sai Nafi'u ya ce: "Karya suke mini, amma zan faɗa maka yadda abin yake. Ibn Umar ya karanta mini Alƙur'ani wata rana har ya zo ga faɗar Allah Ta'ala: "Matanku gonaki ne agare ku...." sai ya ce: "Nafi'u ka san labarin wannan ayar? Mu mutanen ƙabilar Kuraishawa mun kasance muna tarawa da matanmu ta hanyar goho, lokacin da muka zo Madina, muka auri matan Madina, sai muka nemi mu yi abin da muka saba yi da matanmu da su, sai suka ƙi yarda, kuma suka ɗauki abin da girma, domin su matan Madina mazajensu suna saduwa da su ne ta rigingine, sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Matanku gonaki ne a gare ku, don haka ku zaike wa gonakinku ta inda kuka ga dama." [An-Nasa'i, *As-Sunan Alkubr*a #8978, At-Tahawi, *Sharhu Ma'anil Athar*, #4067].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa da kada su mayar da rantsuwa da Allah wani shamaki da za su fake da shi su ƙi aikata ayyukan alheri, kamar biyayya ga iyaye ko taimaka wa dangi da mabuƙata ko su yi rantsuwar da za ta hana su sulhu tsakanin mutane, kamar mutum ya rantse cewa, shi ba zai yi abu kaza ba na alheri, idan an zo an nemi da ya yi wannan abu sai ya ce ai ya riga ya rantse ba zai yi ba, don haka a ƙyale shi. Idan har hakan ta faru, to wannan kada ya hana shi aikata alheri, abin da zai yi shi ne, kawai ya karya wannan rantsuwar, ta hanyar aikata abin da ya ce ba zai aikata ba, sannan ya yi kaffarar rantsuwarsa. Allah yana jin kowa, ya san kuma niyyar kowa, mai kyau da marar kyau.

An karɓo daga Abu Hurairata (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Wani mutum ya kai dare a wajen Annabi (ﷺ), da ya koma gida sai ya sami yaransa duk sun yi barci, sai matarsa ta kawo masa abinci, sai ya rantse da Allah ba zai ci ba, saboda yaran nasa, sannan daga baya ya canza ra’ayi ya ɗauki abincin ya ci. Da gari ya waye ya zo ya faɗa wa Annabi (ﷺ) abin da ya faru, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wanda duk ya yi rantsuwa, sannan ya ga abin da ya rantse a kansa waninsa ya fi shi alheri, to ya aikata wannan da ya fi shi alherin, ya yi kaffarar rantsuwarsa.” [Muslim #1650].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abin la'akari a game da rantsuwa shi ne abin da mutum ya ƙudurce a zuciyarsa.

2. Zukata suna da ayyuka kamar yadda gaɓoɓi suke da ayyuka.

3. Duk wanda ya yi rantsuwar ƙarya ko ya yi rantsuwa ya karya da gangan, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai kama shi da laifin aikata haka.

Suratul Baƙara (225)

لَّا يُؤَاخِذُكُمُ ٱللَّهُ بِٱللَّغۡوِ فِيٓ أَيۡمَٰنِكُمۡ وَلَٰكِن يُؤَاخِذُكُم بِمَا كَسَبَتۡ قُلُوبُكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ حَلِيمٞ ٢٢٥

225. Allah ba zai kama ku da yasasshen zance a cikin rantse-rantsenku ba, sai dai zai kama ku da abin da zukatanku suka ƙudurce. Kuma Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan haƙuri.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin hukuncin rantsuwa; ya bayyana cewa, ba ya kama bayinsa a kan yasasshiyar rantsuwa da suke yi, irin wadda bakunansu suka saba yi cikin wasu al’amuransu, ba tare da suna nufin rantsuwar ita kanta ba. Ko kuma rantsuwar da mutum zai yi a kan wani abu da yake da ƙwaƙƙwaran zato haka yake, sai kuma daga baya ya bayyanar masa cewa ba haka abin yake ba. Allah ya ce ba zai kama bayinsa da laifin irin waɗannan rantse-rantse ba; sai dai zai kama su da duk wata rantsuwar da za su yi ta ƙarya. Amma ga wanda ya yi rantsuwar ba zai yi abu kaza ba, ko sai ya yi abu kaza, sannan ya karya rantsuwar, to zai yi kaffarar rantsuwa a nan duniya, idan kuwa bai yi ba, to zai gamu da uƙubar ranar lahira. Allah mai gafara ne, kuma mai haƙuri ne, ba ya gaggauta musu uƙuba saboda ƙarancin ladabinsu wajen yawan rantse-rantse da sunansa cikin al’amarinsu, kuma ba ya fushi da su a kan hakan.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramun ne mutum ya riƙa zaluntar matarsa, kamar yadda Larabawa suka riƙa yi a zamanin Jahiliyya, idan ɗayansu matarsa ta fusata shi sai ya rantse ba zai ƙara kusantar ta ba, wani lokaci ya shafe shekara ɗaya ko shekara biyu ba tare da ya kusance ta ba, bai kuma sake ta ta yi wani auren ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haramta wannan mummunar al'ada ta zalunci, ya sanya wa duk wani wanda ya yi irin wannan rantsuwa ƙayyadajjen lokaci na wata huɗu; ko dai ya dawo ya ci gaba da mu'amalar aure da matarsa ko kuma ya sake ta bayan ƙarewar wata huɗu.
2. Rashin dacewar rantsuwar *ila'i* a zamantakewar aure. Amma wani lokaci babu laifi mutum ya ƙaurace wa matarsa da nufin ladabtarwa kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya taɓa ƙaurace wa matansa tsawon wata guda bayan sun matsa masa a kan maganar ƙarin ciyarwa da sanya shi ya haramta wa kansa kuyangarsa Mariya da shan zuma.

3. Wanda ya yi rantsuwa ba zai kusanci matarsa ba an tsawon lokaci ƙasa da wata huɗu, to ba za a yi masa hukucin *ila'i* ba, watau ba za a tilasta masa lallai sai ya zaɓi koma wa ga matarsa ba ko kuma a ce ya sake ta.

4. Barin abin da ya bayyana na kuskure da kama gaskiya yana jawo wa bawa gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Saki a hannun miji yake ba a hannun mace ba.

Suratul Baƙara (226-227)

لِّلَّذِينَ يُؤۡلُونَ مِن نِّسَآئِهِمۡ تَرَبُّصُ أَرۡبَعَةِ أَشۡهُرٖۖ فَإِن فَآءُو فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٢٦ وَإِنۡ عَزَمُواْ ٱلطَّلَٰقَ فَإِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٢٢٧

226. Waɗanda suke rantsuwar ba za su sadu da matansu ba, za a yi musu jinkiri na wata huɗu; to idan sun dawo, to lalle Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.

227. Idan kuwa suka yi niyyar saki (a cikin zukatansu), to lalle Allah Mai ji ne, kuma Masani.

To bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin hukuncin rantsuwa a dunƙule, sai kuma ya zo da bayanin wata rantsuwa ta musamman da miji yake yi a kan matarsa, wadda ake kira *ila'i*, wato mutum ya rantse cewa ba zai kusanci matarsa ba; sai Allah ya bayyana hukuncinta da cewa, an ba shi wata huɗu ne, idan ya dawo ya ci gaba da hulɗar aure da matarsa kafin ƙarewar wannan wa'adi da aka ba shi, ko kuma daidai lokacin da watannin suka cika, to shi ke nan magana ta ƙare, sai su ci gaba da zaman aurensu. Allah mai gafara ne a gare shi a kan wannan lokacin da ya shafe ba tare da kusantar matarsa ba, sannan mai rahama ne gare shi, ta yadda ya bar masa aurensa, ba tare da ya ɗora masa kaffarar rantsuwa ba.
Idan kuma har ya zamanto yana nufin saki ne da wannan rantswar, to ya yi gaggawar sakin wannan mata, ba tare da ya cutar da ita ba, ta hanyar watsi da ita har wani tsawon lokaci, domin Allah mai ji ne, yana jin sakin da zai yi mata, yana kuma sane da abin da ya ƙulla a zuciyarsa na niyyar sakin, babu abin da yake ɓuya gare shi (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Anas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) Ya yi rantsuwar ƙaurace wa matansa (wata ɗaya). A daidai lokacin kuma ya gurɗe a ƙafa, sai ya zauna a wani ɗakin benensa tsawon kwana ashirin da tara, sannan ya sauko. Sai matansa suka ce masa: "Ya Manzo Allah, ka yi rantsuwar ƙauracer wa wata ɗaya ne". Sai ya ce: "Ai wata yakan zamanto kwana ashirin da tara." [Bukhari #1911].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An danƙa wa mata amanar bayanin abin da yake cikin mahaifarsu, kuma su ne madogara wajen sanin ƙarewar wa'adin idda da haila ko da tsarki.

2. Tsoratarwa da ranar lahira a kan faɗar abin da ba gaskiya ba.
3. Wajibi ne a kan matar da aka saka ta faɗi gaskiya game al'adarta ko kwanakin iddarta ba tare da ƙari ko ragi ba.

4. Yaƙi da son zuciya a kan munanan manufofi, domin matar da mijinta ya sake ta za ta iya yin ƙaryar kammala idda domin ta gaggauta rabuwa da shi, don hana masa haƙƙin kome da shari'a ta ba shi, ko

kuma ta ƙara lokacin iddarta da gangan don mijin ya daɗe yana ɗaukar nauyin ciyar da ita, ko ta ɓoye cikinta don ta auri wani da shi, ta mayar da ɗan wani ɗansa. Da sauran miyagun manufofi irin waɗannan.

5. Kiran wanda ya saki matarsa da suna 'miji' yana nuna igiyar aurensu ba za ta yanke ba har sai ta fita daga idda, sai dai idan saki *ba'ini* ne, watau wanda babu kome a cikinsa, kamar saki na uku.

6. Wajibi ma'aurata biyu su ba wa juna haƙƙoƙinsu.

7. Rushe aƙidar daidaito tsakanin miji da matarsa, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya danƙa shugabanci a hannun miji, ya fifita shi a kan matarsa, don haka ya zama dole a kanta ta girmama mijinta tare da yi masa biyayya a kan duk wani umarni nasa da bai saɓa wa na Allah da Manzonsa ba, domin Allah ya fifita shi wajen hankali da hangen nesa, ya kuma ɗora masa nauyin ciyar da iyalinsa da kulawa da su, ya sanya alhakin saki da kome a hannunsa.

8. Kwaɗaitarwa a kan kyautata mu'amalar zamantakewar aure tsakanin miji da matarsa.

9. Haƙƙin kome ga maji yana tattare ne da sharaɗin zai kyautata zamantakewa da ita, ba da niyyar cutar da ita ba.

10. Tunatar da miji buwayar Allah, don tsawatar masa a kan ya kiyayi cutar da matarsa, idan kuwa ba haka ba ya gamu da hushin Allah mabuwayi.

Suratul Baƙara (228)

وَٱلْمُطَلَّقَٰتُ يَتَرَبَّصْنَ بِأَنفُسِهِنَّ ثَلَٰثَةَ قُرُوٓءٍ ۚ وَلَا يَحِلُّ لَهُنَّ أَن يَكْتُمْنَ مَا خَلَقَ ٱللَّهُ فِىٓ أَرْحَامِهِنَّ إِن كُنَّ يُؤْمِنَّ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ ۚ
وَبُعُولَتُهُنَّ أَحَقُّ بِرَدِّهِنَّ فِى ذَٰلِكَ إِنْ أَرَادُوٓا۟ إِصْلَٰحًا ۚ وَلَهُنَّ مِثْلُ ٱلَّذِى عَلَيْهِنَّ بِٱلْمَعْرُوفِ ۚ وَلِلرِّجَالِ عَلَيْهِنَّ دَرَجَةٌ ۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٢٢٨﴾

228. Kuma mata waɗanda aka saki za su dakatar da kawunansu (tsawon) uku, kuma ba ya halatta a gare su su ɓoye abin da Allah Ya halitta a cikin mahaifarsu, in sun kasance suna yin imani da Allah da ranar ƙarshe; kuma mazajensu su suka fi cancantar dawo da su a cikin wancan lokaci in sun yi nufin sulhu; kuma su (mata) suna da haƙƙi kwatankwacin irin wanda yake kansu ta hanyar da aka sani, kuma mazaje suna da fifiko a kansu. Kuma Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.
Wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin matan da mazajensu za su sake su bayan sun tare da su. Ya bayyana cewa, idan waɗannan mata masu yin jinin haila ne, kuma ba sa ɗauke da ciki, to yayin da aka sake su, kada su yi gaggawar yin wani auren; a'a, za su jira tsawon *kuri* uku.
Kur'i kalama ce wadda a harshen Larabci tana nufin 'haila' tana kuma nufin 'tsarki', don haka malamai suka yi saɓani wajen tantance ma'anar ta wannan ayar; sai dai a ra'ayin manyan sahabbai daga cikinsu har da halifofin Annabi huɗu, da manyan tabi'ai da wasu daga cikin manyan malamai suna ganin ma'anar kalmar a wannan wuri shi ne 'jinin haila'. Watau idan mutum ya saki matarsa, to iddar ta tana ƙare wa ne da ɗaukewar jinin al'adar ta ta uku bayan sakin.
Kuma haramun ne a kansu su ɓoye batun hailarsu ko batun cikinsu, saboda ɓarnar da yin hakan zai haifar. Domin idan ta ɓoye hakan, wannan zai iya jawo jingina ɗa ba ga ubansa ba, wanda kuma wannan yana tattare da matsaloli masu tarin yawa da za su shafi yanke zumunci da gado da auratayya da sauransu. Hakanan ɓoye hailarta, ko ta ba da labarin cewa ta yi jini, alhalin ƙarya take, wannan zai haifar da hana mijinta haƙƙinsa na kome, da halatta aurenta ga wani mijin ba shi ba kafin lokacinsa ya yi; yin haka shi ma zai haifar da irin waccan ɓarna da aka ambata a baya. Ko kuma ta yi ƙaryar ba ta yi jini ba, domin ta ci gaba da karɓar kuɗin ciyarwa, alhali ba haƙƙinta ba ne, wataƙila mijinta ya dawo da ita bayan

kuma iddarta ta riga ta ƙare, ya zamana suna zaman zina a tsakaninsu. To irin wannan aiki babu matar da za ta yi shi, sai wadda ba ta yi imani da Allah da ranar lahira ba. Kuma mazajensu su ne suke da haƙƙin dawo da su kafin gama wa'adin iddarsu, matuƙar suna son su ci gaba da zama na ƙauna da mutuntawa a tsakaninsu. Wannan hukunci ya taƙaita a kan matar da mijinta ya yi mata saki na ɗaya ne ko na biyu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi batun haƙƙin matayen aure a kan mazajensu da haƙƙin mazajensu a kansu, ya bayyana cewa, wajibi ne a kan kowanne ɓangare ya kiyaye haƙƙin ɗaya ɓangaren, kada wani ya zalunci wani, kuma maza suna da fifiko a kan matansu wajen girman haƙƙi da biyayya.
Allah shi ne mai cikakken iko da buwaya, don haka yana iya yi wa duk wanda ya saba wa dokarsa horo, sannan mai hikima ne cikin duk hukunce-hukuncen da ya shar'anta wa bayinsa.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga mace da ya sanya saki ba ya wuce uku, ya kuma haramta wa miji dawo da matarsa don cutar da ita, ko ya sake ta tare da cutar da ita.

2. Musulunci ya yi umarnin kyautata wa mace, ko da kuwa an zo rabuwa ne, ballatana tana gidan mijinta na aure.

3. Ba ya halatta ga mace ta nemi *khul'i* a wajen mijinta alhalin suna zaman lafiya ba tare da wani aibi ba.

An karɓo daga Sauban (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk matar da ta nemi mijinta ya sake ta ba tare da wani laifi ba, to ƙamshin Aljanna ya haramta a gare ta." [Abu Dawud #2226, da Tirmizi #1187, da Ibn Maja #2055].
A wani lafazin ya ce: "Mata masu neman *khul'i* su ne munafukai." [Timizi #1186].

4. Ba ya halatta ga miji ya karɓi kuɗin *'khul'i* fiye da yadda ya ba ta lokacin aurenta.

5. Ba ya halatta ga miji ya tilasta wa matarsa biyan kuɗin *khul'i* don kawai ya sake ta ba tare da ta nemi hakan daga gare shi ba.

6. Mafi ingancin magana ita ce, *khul'i ba* saki ba ne, warware aure ne, matar da ta yi *khul'i za* ta yi idda ne da haila ɗaya kamar yadda ya tabbata a hadisi.

7. Halaccin miji ya sake auren matar da ya yi wa saki uku bayan sun cika sharuɗɗa kamar haka:
Wani mijin ya aure ta bayan ta gama idda.
Aurenta na biyu ya zamo ingantaccen aure.
Ya zamanto ya aure ta ne don yana son ta, yana kuma nufin zama da ita, ba auren kisan wuta ba.
Ya zamanto ya sadu da ita bayan ya aure ta.
Idan mijinta na biyu ya sake ta, to mijinta na farko yana da damar ya sake auren ta bayan ta gama iddar mijinta na biyu.

Suratul Baƙara (229-230)
ٱلطَّلَٰقُ مَرَّتَانِۖ فَإِمۡسَاكُۢ بِمَعۡرُوفٍ أَوۡ تَسۡرِيحُۢ بِإِحۡسَٰنٖۗ وَلَا يَحِلُّ لَكُمۡ أَن تَأۡخُذُواْ مِمَّآ ءَاتَيۡتُمُوهُنَّ شَيۡـٔٗا إِلَّآ أَن يَخَافَآ أَلَّا يُقِيمَا حُدُودَ ٱللَّهِۖ
فَإِنۡ خِفۡتُمۡ أَلَّا يُقِيمَا حُدُودَ ٱللَّهِ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡهِمَا فِيمَا ٱفۡتَدَتۡ بِهِۦۗ تِلۡكَ حُدُودُ ٱللَّهِ فَلَا تَعۡتَدُوهَاۚ وَمَن يَتَعَدَّ حُدُودَ ٱللَّهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ

ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢٢٩﴾ فَإِن طَلَّقَهَا فَلَا تَحِلُّ لَهُۥ مِنۢ بَعۡدُ حَتَّىٰ تَنكِحَ زَوۡجًا غَيۡرَهُۥۗ فَإِن طَلَّقَهَا فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡهِمَآ أَن يَتَرَاجَعَآ إِن ظَنَّآ أَن يُقِيمَا حُدُودَ ٱللَّهِۗ وَتِلۡكَ حُدُودُ ٱللَّهِ يُبَيِّنُهَا لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ﴿٢٣٠﴾

229. Saki sau biyu ne (ɗaya bayan ɗaya), don haka ko dai ya riƙe ta ta hanyar da aka sani, ko kuma ya sake ta tare da kyautatawa. Kuma bai halatta gare ku ba ku karɓi wani abu daga cikin abin da kuka ba su, sai fa idan su (ma'aurata) biyu sun ji tsoron ba za su tsayar da dokokin Allah ba. To idan kuka ji tsoron ba za su tsayar da dokokin Allah ba, to babu laifi a gare su game da abin da ta fanshi kanta da shi. Waɗannan iyakokin Allah ne, kada ku ƙetare su, kuma duk wanda ya ƙetare iyakokin Allah, to waɗannan su ne azzalumai.

230. To idan ya sake sakin ta, ba za ta halatta a gare shi ba bayan haka har sai ta auri wani mijin daban. To idan ya sake ta, to babu laifi gare su su koma, idan sun yi zaton cewa za su tsayar da dokokin Allah. Waɗannan dokokin Allah ne, Yake bayyana su ga mutanen da suke da sani.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, sakin da miji yake da haƙƙin kome, shi ne sakin farko da na biyu kawai, saɓanin yadda suke yi a zamanin jahiliyya, mutum ya yi ta sakin matarsa yana dawo da ita ba iyaka. Sai Allah ya yi wa tufkar hanci. Don haka idan mutum ya yi wa matarsa saki biyu, kuma ba ta gama iddarta ba, to yana da zaɓi ya dawo da ita su ci gaba da zaman gaskiya, ba cuta ba cutarwa, ko kuma ya ƙyale ta har ta gama iddarta, su rabu cikin mutunci, ba tare da ya cutar da ita ba. Idan sakin ya zaɓa, to bai halatta a gare shi ya karɓi wani abu da ya ba ta na sadaki ko waninsa ba. Sai dai idan akwai tsoro ta ɓangarensa, ko ta ɓangaren matar, cewa idan suka ci gaba da rayuwar aure, to wani daga cikinsu ba zai kula da haƙƙin abokin zamansa ba, to a wannan lokaci ya halatta ta mayar masa abin da ya ba ta domin su rabu. Babu laifi a kanta, idan ta yi hakan, shi ma ba ya da laifi idan ya karɓa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Matar Sabitu ɗan Kaisu (Allah ya kara masa yarda) ta zo wurin Annabi (ﷺ) ta ce: "Ya Manzon Allah, ba na zargin Sabitu a addininsa da ɗabi'unsa, sai dai ba zan iya zaman aure da shi ba." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce mata: "To za ki mayar masa da gonarsa da ya ba ki?" Sai ta ce: "E". Sai ya ce wa Sabitu: "Ka karɓi gonarka ku rabu". [Bukhari#5273, 5274, 5276].

An karɓo daga Rabiyyi' 'yar Mu'awwiz ɗan Afra (Allah ya kara mata yarda) cewa, ta yi *khul'i* tsakaninta da mijinta a zamanin Manzon Allah (ﷺ), sai Manzon Allah (ﷺ) ya umarce ta ta yi idda da haila ɗaya. [Tirmizi#1185, da Ibn Maja #2058].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk waɗannan hukunce-hukunce iyakokinsa ne, bai halatta muminai su tsallake su ba bayan ya bayyana su a gare su filla-filla, wanda duk ya tsallake wani hukunci daga waɗannan hukunce-hukunce, to babu shakka ya zama azzalumi na haƙiƙa, domin ya aikata abin da ya haramta a gare shi ya aikata.
To idan kuma mutum ya yi wa matarsa saki na uku, to ta haramta a kansa, ba shi da damar yin kome, har sai ta auri wani mijin daban, kuma ya sadu da ita. To idan mijin na biyu ya sake ta, ta gama iddarta, babu laifi tsohon mijinta ya sake auren ta, bayan sun tabbatar cewa za su yi zaman aure tare da mutunta juna da kula da haƙƙin juna. Duk waɗannan hukunce-hukunce da suka gabata, Allah yana bayyana su ga masu ilimi, domin su ne za su fahince su, kuma su fahintar da wasu, da haka kowa sai ya amfana da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba ya halatta ga mijin da ya saki matarsa saki na farko na biyu ya dawo da ita da niyyar cutar da ita.

2. Idan miji ya kasa ciyar da matarsa, ita kuma ta kasa yin haƙuri, to dole ne ya sawwaƙe mata, domin ya kasa riƙe ta ta hanyar da ta dace da shari'a.

3. Duk wanda yake saɓa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to lalle yana zaluntar kansa ne, domin yana jefa kansa ne cikin hushin Allah da uƙubarsa.

4. Haramcin yin izgili da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Wajabcin godiya a kan ni'imomin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Alƙur'ani da sunnar Annabi (ﷺ) babbar ni'ima ce ga Musulmi, don haka ya wajaba ga duk wani Musulmi ya san su ya kuma rungumi aiki da su.

Suratul Baƙara (231)

وَإِذَا طَلَّقْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَبَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَأَمْسِكُوهُنَّ بِمَعْرُوفٍ أَوْ سَرِّحُوهُنَّ بِمَعْرُوفٍ ۚ وَلَا تُمْسِكُوهُنَّ ضِرَارًا لِّتَعْتَدُوا۟ ۚ وَمَن يَفْعَلْ ذَٰلِكَ فَقَدْ ظَلَمَ نَفْسَهُۥ ۚ وَلَا تَتَّخِذُوٓا۟ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ هُزُوًا ۚ وَٱذْكُرُوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَمَآ أَنزَلَ عَلَيْكُم مِّنَ ٱلْكِتَٰبِ وَٱلْحِكْمَةِ يَعِظُكُم بِهِۦ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٢٣١﴾

231. Kuma idan kuka saki mata, sai wa’adin iddarsu ya kusa, (idan kuna son su) sai ku riƙe su ta hanyar da ta dace (a shari'ance) ko kuma ku ƙyale su ta hanyar da ta dace (a shari'ance); kuma kada ku riƙe su da nufin cutarwa don ku ƙetare iyakar (Ubangiji). Duk wanda ya aikata haka kuwa, to haƙiƙa ya zalunci kansa. Kuma kada ku mayar da ayoyin Allah abin izgili, kuma ku tuna ni'imar Allah da Ya yi muku da abin da Ya saukar muku na Littafi da Hikima Yana yi muku wa'azi da shi. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani lalle Allah Masanin komai ne.

Haka kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara jawo hankalin maza cewa, idan sun saki matansu, har suka kusa kammala wa’adin iddarsu, to ko dai su dawo da su, idan za su kiyaye musu haƙƙinsu na aure, ko su ƙyale su su kammala wa’adin iddarsu, ba tare da sun cutar da su ba. Allah ya hana cutar da mata masu idda ta hanyar dawo da su yayin da suka kusa kammala iddarsu, da niyyar tsawaita musu iddarsu, ko kuma don kada su auri wasu mazajen, ko kuma don tursasa musu sai sun biya *khul’i don* su fanshi kawunansu; yin haka ta’addanci ne gare su, kuma wanda duk ya yi irin haka, to ya zalunci kansa, domin daga ƙarshe shi ne mai cutuwa ta hanyar zunubi da yake ɗaukar wa kansa, da kuma uƙubar Allah da yake jawo wa kansa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana ɗaukar abin da Allah ya saukar na hukuce-hukunce, abin yi wa izgili, ko wasa da shi, ya umarci bayinsa su tuna ni’imomin Allah da ya yi musu, waɗanda ba za su lissafu ba, daga cikinsu har da wahayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabinsa (ﷺ), wanda ya haɗa da Alƙur’ani da sunnar Annabi (ﷺ), waɗanda da su ne Allah yake yi musu wa’azi da tunatarwa. Sannan Allah ya umarce su da su kiyaye dokokinsa ta hanyar aiwatar da umarninsa da guje wa haninsa, kuma su sani cewa ilimin Allah ya kewaye komai, babu wani abu da bai san da zamansa ba.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk auren da aka yi shi a cikin idda lalataccen aure ne.

2. Yarda da amincewar ma'aurata biyu muhimmin abu ne a cikin ingancin aure.

3. Ba ya halatta ga waliyyin mace ya aurar da ita ba tare da yardarta da amincewarta ba.

4. Idan mace ta yarda ta auri wanda bai dace da ita ba a shari'ance, kamar ya zamo fasiƙi ne ko mai gurɓatacciyar aƙida, to waliyyinta yana da haƙƙin ya hana ta auren sa.

5. Yana da kyau waliyyai su yi la'akari da nadamar ma'aurata biyu bayan saki ya auku, su bar su su koma zaman aurensu.

6. Aiki da hukunce-hukuncen shari'a yana tsarkake zuciya ya kuma haɓaka imani.

Suratul Baƙara (232)

وَإِذَا طَلَّقْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَبَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَلَا تَعْضُلُوهُنَّ أَن يَنكِحْنَ أَزْوَٰجَهُنَّ إِذَا تَرَٰضَوْا۟ بَيْنَهُم بِٱلْمَعْرُوفِ ۗ ذَٰلِكَ يُوعَظُ بِهِۦ مَن كَانَ مِنكُمْ يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْـَٔاخِرِ ۗ ذَٰلِكُمْ أَزْكَىٰ لَكُمْ وَأَطْهَرُ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿٢٣٢﴾

232. Kuma idan kun saki mata sai suka cika wa’adin iddarsu, to (ku waliyyai) kada ku hana su su auri mazajensu (na da) idan sun yi yarjejeniya a tsakaninsu ta hanyar da ta dace (a shari’a). Wannan (abin da aka ambata) shi ne wanda ake yin wa'azi da shi ga wanda ya kasance daga cikinku, yana imani da Allah da ranar lahira. Wannan shi ne abin da ya fi alheri a gare ku kuma ya fi tsarki; kuma Allah Shi ne Yake da sani, ku ba ku sani ba.

A wannan ayar kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana waliyyan matan da suka kammala iddarsu, su takura musu, su hana su sake auren mazajensu na da, waɗanda suka yi musu sakin kome, muddin sun yarda su koma su ci gaba da rayuwar aure a tsakakaninsu, tare da kiyaye wa juna haƙƙi da zaman mutunci. Wannan hani Allah yana yin sa ne kuma yana tsawatar da duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira. Kuma waliyyan matan su yi aiki da wannan doka, su bar hana mata sake auren mazajensu na da. Wannan shi ne ya fi musu alheri a wajen Allah, kuma shi ne abin da zai tsarkake musu zukatansu daga gaba da ƙiyayya, kamar yadda shi ne abin da zai tsare musu mutuncinsu da na ‘ya’yansu. Allah ne ya fi sanin abin da zai amfani bayinsa a duniya da lahira. Amma bayi ba su san a ina alherin yake ba, sai abin da Allah ya sanar da su, saboda haka ya wajaba su sallama wa Allah hukunce-hukuncensa, su yi biyayya gare shi ba ga soye-soyen zukatansu ba.
An karɓo da Ma'aƙil ɗan Yasar (Allah ya kara masa yarda) cewa, ya aurar da 'yar'uwarsa ga wani mutum Musulmi a zamanin Annabi (ﷺ), suka zauna tare na wani ɗan lokaci sai ya yi mata saki ɗaya, bai kuma dawo da ita ba har ta ƙare iddarta. Sai daga baya ya dawo yana son ta ita ma kuma tana son sa, sai ya shiga cikin manema auren ta, sai Ma'aƙil ya ce masa: "Ya marar mutunci, na mutunta ka na aurar maka, amma sai ka wulaƙanta ta ka sake ta, to wallahi har abada ba za ta sake koma wa gidanka ba." Sai Allah ya san buƙatar mijinta gare ta da buƙatarta ta koma wa gidan mijinta, sai ya saukar da wannan ayar. [Bukhar i#5130, da Abu Dawud #2087, da Tirmizi #2981].

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shari'ar Musulunci shari'a ce da take kula da haƙƙoƙin ƙananan yara.

2. Haƙƙin uwa ne ta shayar da ɗanta ko da bayan sun rabu da mahaifin yaron.

3. Cikar wa'adin shayarwa shi ne shekaru biyu cikakku. Babu laifi a rage ƙasa da haka bayan yarjejeniyar mahaifan biyu.

4. Ba ya halatta uwa ko uba wani daga cikinsu ya yi gaban kansa wajen yaye yaro ba tare da shawara da yarjejeniya a tsakaninsu ba.

5. Ba ya halatta ga wata uwa ta ƙi shayar da ɗanta tare da cewa babu wadda take shayar da shi, domin masalahar kanta kawai, kamar kwalliyar jikinta, idan kuwa har ta aikata haka, to ta zama azzalumar uwa.

6. Matar da mijinta ya sake ta tana shayar masa da ɗansa, to wajibi ne a kansa ya ciyar da ita ya shayar da ita har sai ta yaye shi.

Suratul Baƙara (233)

۞ وَٱلۡوَٰلِدَٰتُ يُرۡضِعۡنَ أَوۡلَٰدَهُنَّ حَوۡلَيۡنِ كَامِلَيۡنِۖ لِمَنۡ أَرَادَ أَن يُتِمَّ ٱلرَّضَاعَةَۚ وَعَلَى ٱلۡمَوۡلُودِ لَهُۥ رِزۡقُهُنَّ وَكِسۡوَتُهُنَّ بِٱلۡمَعۡرُوفِۚ لَا تُكَلَّفُ نَفۡسٌ إِلَّا وُسۡعَهَاۚ لَا تُضَآرَّ وَٰلِدَةُۢ بِوَلَدِهَا وَلَا مَوۡلُودٞ لَّهُۥ بِوَلَدِهِۦۚ وَعَلَى ٱلۡوَارِثِ مِثۡلُ ذَٰلِكَۗ فَإِنۡ أَرَادَا فِصَالًا عَن تَرَاضٖ مِّنۡهُمَا وَتَشَاوُرٖ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡهِمَاۗ وَإِنۡ أَرَدتُّمۡ أَن تَسۡتَرۡضِعُوٓاْ أَوۡلَٰدَكُمۡ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡكُمۡ إِذَا سَلَّمۡتُم مَّآ ءَاتَيۡتُم بِٱلۡمَعۡرُوفِۗ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ٢٣٣

233. Kuma iyaye mata za su shayar da 'ya'yansu tsawon shekara biyu cikakku, ga wanda ya yi nufin ya cika wa'adi na shayarwa. Kuma wajibi ne a kan wanda aka yi wa haihuwa ya ciyar da su (mata masu shayarwa) da yi musu tufafi ta hanyar da aka saba. Ba a ɗora wa wani rai sai abin da zai iya. Kar a cutar da uwa saboda ɗanta, haka kuma kar a cutar da uba saboda ɗansa. Kuma kwatankwacin irin wannan ya wajaba kan magajinsa. To idan su biyun sun yi nufin yaye bisa ga yarjejeniya da shawara da junansu, to babu laifi a kansu. Kuma idan kun yi nufin nema wa 'ya'yanku mai shayarwa, to babu laifi a kanku idan kun bayar da abin da ya kamata ta yadda aka saba. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku sani cewa, lalle Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

Bayan rabuwa ta tabbata tsakanin miji da mata, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara an samu haihuwa a tsakaninsu, to a nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai bar al’amarin yaron da aka samu tsakanin waɗannan ma’aurata su yi yadda suka ga dama ba, sai ya saukar da hukuncin shayarwa da bayanin nauyin da yake kan uwa da uba dangane da ɗansu da yake shan nono. Allah ya umarci iyaye mata da su shayar da ‘ya’yansu tsawon shekara biyu cur, idan har uwar da uban suna da buƙatar hakan, ko shi uban shi kaɗai, ko ita uwar ita kaɗai, waninsu ya buƙaci cika wa’adin shayarwa. To a yayin wannan shayarwa dole ne uba ya ɗauki nauyin ci da shan uwar da tufatar da ita gwargwadon yadda ya dace a al’adance, ba tare da almubazzaranci ba, kuma ba tare da ƙwauro ba. Allah ba ya ɗora wa mutum sai abin da zai iya ɗauka. Sannan ya bayyana cewa haramun ne ita uwa ta ƙi karɓar shayar da ɗanta ko ta nemi sai an biya ta fiye da ladanta domin kawai ta cutar da uban yaron. Kamar yadda Allah ya haramta wa uban yaro ya hana uwarsa ta shayar da shi, don kawai ya cutar da ita.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta wa wanda yake da gadon yaron da ubansa ya rasu, irin abin da ya wajabta wa shi uban na ciyarwa da tufatarwa ga uwar yaron, ba tare da cutar da ita

ba. Sannan Allah ya halatta wa iyayen yaro yaye ɗansu kafin cikar shekara biyu, bayan sun yi shawara a tsakaninsu, sun yarda da hakan, saboda wata maslaha da suka hango ta shi yaron. Hakanan Allah ya halatta wa iyaye maza su nemo wa ‘ya’yansu masu shayar da su, amma ba da nufin cutar da iyayen yaron ba, sai don wani dalili na daban. To idan ya yi haka babu laifi bayan ya biya jingar shayarwa ga ita mai shayarwa, ya biya ta haƙƙinta cib-cib, ba tare da ya rage mata komai ba. Sannan Allah ya yi umarni da a kiyaye dokokinsa ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da shi, da barin abin da ya hana, kuma bayinsa su san da cewa babu wani abu da yake ɓoye gare shi, yana ganin duk ayyukansu masu kyau da marasa kyau, kuma zai yi musu sakayya a kai.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matar da mijinta ya rasu wajibi ne a kanta ta yi masa iddar takaba tsawon wata huɗu da kwana goma. Wannan hukunci ya shafi duk wata mata da mijinta ya rasu, babba ce ko yarinya ƙarama; ko 'ya ko baiwa; ko ta tare da mijin ko ba ta tare da shi ba, duka ɗaya ne.

2. Yadda Musulunci ya girmama 'ya mace ya kuma tausya mata, ba kamar yadda ta kasance a da zamanin Jahiliyya ba, a lokacin da ake rufe ta a wani ɗan ƙaramin ɗaki mai cike da ƙazamta har tsawon shekara ɗaya cur tana sanye da riga ɗaya, ba tare da an ƙyale ta ta sanya turare ko wani abin ƙamshi a jikinta ba. Bayan ta shekara ɗaya a wannan mummunan yanayi sai a zo mata da wani tsuntsu sai ta shafe jikinta da shi, wanda sau da dama tsananin warinta yakan kashe shi. Sai kuma a ba ta kashin raƙumi ta jefa shi bayanta, ko kuma idan wani kare ya zo gilamawa ta gabanta sai ta jefe shi da shi, domin wai ta nuna cewa zamanta bayan rasuwar mijinta ya fi kashin raƙumin da za a jefi kare da shi ƙaskanci. To idan ta yi haka ta fita daga iddar takaba. Sai Musulunci ya zo ya rushe wannan mummunar al'ada.

3. Girman haƙƙin miji a kan matarsa ne ya sa za ta zauna a gida bayan rasuwarsa tsawon wata huɗu da kwana goma ba tare da yin kwalliya ba.

4. Nauyin da yake kan iyaye na hana 'ya'yansu mata aikata abin da ya saɓa wa shari'a.

Suratul Baƙara (234)

وَٱلَّذِينَ يُتَوَفَّوْنَ مِنكُمْ وَيَذَرُونَ أَزْوَٰجًا يَتَرَبَّصْنَ بِأَنفُسِهِنَّ أَرْبَعَةَ أَشْهُرٍ وَعَشْرًا ۖ فَإِذَا بَلَغْنَ أَجَلَهُنَّ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ فِيمَا فَعَلْنَ فِىٓ أَنفُسِهِنَّ بِٱلْمَعْرُوفِ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿٢٣٤﴾

234. Kuma waɗanda suka mutu daga cikinku, suka kuma bar mata na aure, (su matan) za su yi zaman jira na wata huɗu da kwana goma. To idan sun cika wa’adinsu, babu laifi a kanku (waliyyansu) cikin duk abin da suka aikata game da kawunansu ta hanyar da aka saba (a shari'a). Kuma Allah Mai cikakken sani ne game da abin da kuke aikatawa.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da bayanin iddar takaba da cewa, idan mutum ya rasu, to wajibi ne a kan matarsa ta yi takabar mutuwarsa, wato ta zauna tsawon wata huɗu da kwana goma a gidan mijinta, ba tare da kwalliya ba, ko saka turare ko fita daga gida ba tare da wata larura ba. Wannan idan matar ba mai ciki ba ce. Idan tana da ciki, to takabarta za ta ƙare ne da zarar ta haihu. To idan har ta fita daga takaba, babu wani laifi a kan waliyyanta don sun bar ta ta yi ado ko ta fita daga gidanta, ko ta sa turare ko ta yi wani auren. Allah yana sane da duk wani abu da mutane suke aikatawa a fili ko a ɓoye kuma zai saka wa kowa gwargwadon yadda ya kiyaye dokokinsa.

An karɓo daga Zainab 'yar Ka'ab ɗan Ujra, ta ce: Furai'a 'yar Malik ɗan Sinan, watau 'yar'uwar Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya kara masa yarda) ta ba ta labari cewa, ta je wurin Manzon Allah (ﷺ) tana tambayarsa cewa ko za ta iya komawa zuwa danginta Banu Khudra, domin mijinta ya fita neman bayinsa da suka tsere, har sai da ya cim masu a wani wuri mai suna *Al-Kadum* sai suka kashe shi a nan. Ga shi kuma mijinta bai bar ta a cikin gida mallakinsa ba bai kuma bar mata abinci ba? Sai Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa mata cewa "E, tana iya tafiya." Ta ce: Sai bayan na juya na tafi har na iso wajen Masallacin Annabi (ﷺ) sai ya sa aka kirawo ni, ya ce mini: "Me ma kika ce?" Sai na maimaita masa abin da na faɗa da farko na al'amarin mijina. Sai ya ce: "Ki zauna a gidanki har sai faralin idda ya cika wa'adinsa". Ta ce: Sai na yi idda a wannan gidan tsawon wata huɗu da kwana goma. Sai a zamani halifancin Usman (Allah ya kara masa yarda) ya aiko yana tambaya ta game da labarina, ni kuma na sanar da shi, sai ya karɓe shi ya yi hukunci da shi.". [Tirmizi #1204, da Nasa'i #3530, da Ibn Maja #2031, da Ahmad #27087, 27363, da Ibn Hibban #1331].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daƙile duk wata hanya da za ta kai mutane zuwa ga aikata haramun. Idan mutum ya bayyana wa mace mai idda aniyarsa ta aure ƙarara, wannan na iya sanya ta ta yi ƙaryar ta gama idda alhali ba ta gama ba, ko ya jefa ta cikin wata fitina.

2. Halaccin mutum ya riya a zuciyarsa cewa zai auri mace mai idda bayan gama iddarta.

3. Bai dace Musulmi ya ɓoye wani abu a zuciyarsa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai yarda da shi ba.

Suratul Baƙara (235)

وَلَا جُنَاحَ عَلَيۡكُمۡ فِيمَا عَرَّضۡتُم بِهِۦ مِنۡ خِطۡبَةِ ٱلنِّسَآءِ أَوۡ أَكۡنَنتُمۡ فِيٓ أَنفُسِكُمۡۚ عَلِمَ ٱللَّهُ أَنَّكُمۡ سَتَذۡكُرُونَهُنَّ وَلَٰكِن لَّا تُوَاعِدُوهُنَّ سِرًّا إِلَّآ أَن تَقُولُواْ قَوۡلٗا مَّعۡرُوفٗاۚ وَلَا تَعۡزِمُواْ عُقۡدَةَ ٱلنِّكَاحِ حَتَّىٰ يَبۡلُغَ ٱلۡكِتَٰبُ أَجَلَهُۥۚ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا فِيٓ أَنفُسِكُمۡ فَٱحۡذَرُوهُۚ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ حَلِيمٞ ٢٣٥

235. Kuma babu laifi a kanku game da abin da kuka yi wa mata jirwaye da shi na neman aurensu ko kuma kuka ɓoye a cikin zukatanku, Allah Ya san cewa ku za ku riƙa maganarsu, sai dai kar ku yi alƙawari da su (na aure) a asirce, sai dai in za ku faɗi zance wanda yake sananne a (shari'a). Kuma kada ku ƙulla igiyar aure (da mata masu takaba) har sai faralin idda ya cika wa’adinsa. Kuma ku sani lalle Allah Ya san abin da yake cikin zukatanku, don haka ku kiyaye Shi. Kuma ku sani lalle Allah Mai yawan gafara ne, Mai haƙuri.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da bayanin hukuncin neman auren mai idda ko mai takaba, da kuma sauran bayanin hukunce-hukuncen saki. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da mace take takaba ko take iddar saki uku, bai halatta ga wani manemi ya fito ƙarara ya bayyana neman aurensa gare ta ba, amma babu laifi ya yi mata jirwaye na neman aurenta. Hakanan babu laifi don ya ɓoye son aurenta a zuciyarsa kafin ta gama iddarta. Allah ya san za su riƙa maganar aurensu yayin da suke cikin idda a bayyane ko a ɓoye, don haka ya ɗauke musu laifin yi musu jirwaye da neman aurensu. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haramta ɗaura auren mace tana cikin idda, har sai ta kammala wa’adin iddarta. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi duk wanda ke da niyyar saɓa wa hukuncinsa, ya bayyana cewa ya san abin da suke ɓoyewa a zukatansu na kwaɗayin auren waɗannan mata masu idda, don haka su guji ɓoye wata aniya wadda ta ci karo da dokar Allah don gudun gamuwa

da uƙubarsa, kuma su sani cewa, Allah mai gafarta wa bayinsa ne idan sun yi laifi sun tuba, mai haƙuri ne, ba ya gaggauto musu da azaba a lokacin da suka saɓa masa, don haka duk sa'adda suka saɓa masa, to su gaggauta tuba, su koma gare shi, zai gafarta musu.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin saki kafin tarewa ko saduwa.

2. Halacin ɗaura aure kafin a ƙayyade sadaki. Bayan miji ya tare da matarsa wadda bai ƙayyade mata sadakinta ba, to zai ba ta sadakin da ake bai wa 'ya mace irinta. Idan kuma ya sake ta kafin ya tare da ita, to dole ne ya yi mata kyautar kwantar da hankali gwargwadon halinsa.

3. Shari'ar Musulunci ba ta ɗora wa mutum abin da ya fi ƙarfinsa.

4. Zahirin wannan aya ya nuna cewa, idan miji bai yanke wa matarsa sadaki ba kuma sai ya sake ta kafin ya sadu da ita, to zai ba ta kyautar kwantar da hankali ne kawai, ko da kuwa ya keɓanta da ita.
To amma Halifofin Annabi (ﷺ) sun shigar da matar da mijin ya yi cikakkiyar keɓe wa da ita cikin wadda za a ba wa cikakken sadaki sun kuma wajabta mata yin idda idan mijin ya sake ta.

An karɓo daga Zurara ɗan Aufa (ﷺ) ya ce: "Hukuncin Halifofi shiryayyu shi ne: Duk wanda ya rufe ƙofa da amaryarsa, ya saki labule, to sadaki da idda sun wajaba." [Baihaƙi, *As-Sunanul Kubra*, Juzu'i na 7, Shafi na 417. Dubi, Al-Albani, *Irwa'ul Ghalil* #1937].

5. Ya halatta mata ta yafe wa mijinta wani abu na sadakinta ko wani ɓangare daga ciki, amma da sharaɗin ta kasance balagaggiya mai hankali mai wayo.

6. Ya halatta mace ta yi kyauta da wani abu na dukiyarta.

7. Kwaɗaitarwa a kan yin afuwa da kyautatawa.

8. Kwaɗaitarwa game da kyautata mu'amala tsakanin 'yan'uwa da guje wa manta kyautatawar da take tsakaninsu.

Suratul Baƙara (236-237)

لَّا جُنَاحَ عَلَيۡكُمۡ إِن طَلَّقۡتُمُ ٱلنِّسَآءَ مَا لَمۡ تَمَسُّوهُنَّ أَوۡ تَفۡرِضُواْ لَهُنَّ فَرِيضَةٗۚ وَمَتِّعُوهُنَّ عَلَى ٱلۡمُوسِعِ قَدَرُهُۥ وَعَلَى ٱلۡمُقۡتِرِ قَدَرُهُۥ مَتَٰعَۢا بِٱلۡمَعۡرُوفِۖ حَقًّا عَلَى ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٢٣٦ وَإِن طَلَّقۡتُمُوهُنَّ مِن قَبۡلِ أَن تَمَسُّوهُنَّ وَقَدۡ فَرَضۡتُمۡ لَهُنَّ فَرِيضَةٗ فَنِصۡفُ مَا فَرَضۡتُمۡ إِلَّآ أَن يَعۡفُونَ أَوۡ يَعۡفُوَاْ ٱلَّذِي بِيَدِهِۦ عُقۡدَةُ ٱلنِّكَاحِۚ وَأَن تَعۡفُوٓاْ أَقۡرَبُ لِلتَّقۡوَىٰۚ وَلَا تَنسَوُاْ ٱلۡفَضۡلَ بَيۡنَكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ٢٣٧

236. Babu laifi (sadaƙi) a kanku idan kun saki mata, matuƙar ba ku riga kun sadu da su ko kuma kun yanka musu sadaki sananne ba. Sai ku yi musu kyauta (ta kwantar da hankali); mai yalwa daidai yalwarsa; talaka ma daidai ƙarfinsa. (Wannan) wata kyauta ce (da za a bayar) ta hanyar da aka saba; haƙƙi ne a kan masu kyautatawa.

237. Idan kuwa kun sake su ne tun kafin ku sadu da su, alhalin kuma kun yanka musu sadaki, to sai (ku bayar) da rabin abin da kuka yanka, sai fa in su matan sun yi afuwa ko kuma wanda a hannunsa igiyar

aure take ya yi afuwa; kuma ku yi afuwa shi ya fi kusa ga taƙawa. Kuma kada ku manta da kyautatawar da take tsakaninku. Lalle Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

A waɗanan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin da ya danganci mutumin da zai auri mace, ya sake ta kafin ya sadu da ita, alhalin bai yanka mata sadaki ba. To a irin wannan yanayi, miji zai yi mata kyauta ta kwantar da hankali gwargwadon ƙarfinsa, da kuma yadda ya dace a shari'ance. Kuma yin wannan kyautar haƙƙi ne a kan duk wanda ya siffantu da siffar kyautatawa ga mutane. Idan kuma ya sake ta ne kafin ya tare da ita, alhalin an riga an yanka mata sadaki, to sai ya ba ta rabin sadakin da aka yanka mata, sai dai idan ta ce ta yafe masa ya riƙe sadakinsa duka, ko kuma shi ya yafe mata, ya bar mata duk sadakin gaba ɗayansa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar da duk ma'auratan cewa, ɗaya ya yi wa ɗaya afuwa, ya bar masa, kuma yin hakan shi ne ya fi kusa da taƙawa. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara jan hankalin ma'auratan da kada su manta kyautatawar da take tsakaninsu. Miji na iya ba wa matarsa fiye da yadda ta cancanta na sadaki, hakanan ita ma matar tana iya yi wa mijinta rangwamen sadaki don tuna alherin da yake tsakaninsu, kuma Allah yana ganin duk ayyukan bayinsa, kuma duk irin aikin da mutum ya yi na alheri, to ba zai faɗi a banza ba, Allah zai yi masa sakayya da alherin da ya fi nasa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jan hankali maza da mata a kan cewa kada su shagala da junansu da tunanin haƙƙoƙinsu har su manta da haƙƙin mahaliccinsu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), musamman abin da ya danganci sallolin farilla biyar.

2. Wajabcin kula da sallolin farilla a lokutansu da kula da rukunansu da wajibansu.3. Falalar sallar la'asar.

4. Wajabcin yin sallolin farilla a tsaye ga wanda yake da ikon tsayuwa.

5. Hana yin magana a salla wadda ba ta danganci gyaran salla ba.6. Halaccin motsi mai yawa a cikin salla yayin larura.

7. Wajabcin kula da lokutan salloli. Dole ne Musulmi ya yi salla a lokacinta gwargwadon ikonsa, kada ya bari lokacin ta ya fita, ko da kuwa zai yi sallar yana tafe ne; ko yana kan abin hawansa; ko a kishingiɗe; ko ta hanyar nuni da kansa; ko ma ba tare da nuni ba idan ya nunin ya gagara; yana da tsarki ne ko ba shi da tsarki; da alwala ko da taimama idan ya gagara yin alwala.

8. Baiwar Allah ga Musulmi da ya sanar da su hukunce-hukuncen addininsa, ba don ya koyar da su ba da ba za su san su ba.

9. Sauƙaƙewar Allah ga bayinsa muminai.

10. Muhimmancin salla a Musulunci.

Suratul Baƙara (238-239)

حَٰفِظُواْ عَلَى ٱلصَّلَوَٰتِ وَٱلصَّلَوٰةِ ٱلۡوُسۡطَىٰ وَقُومُواْ لِلَّهِ قَٰنِتِينَ ٢٣٨ فَإِنۡ خِفۡتُمۡ فَرِجَالًا أَوۡ رُكۡبَانٗاۖ فَإِذَآ أَمِنتُمۡ فَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ كَمَا عَلَّمَكُم مَّا لَمۡ تَكُونُواْ تَعۡلَمُونَ ٢٣٩

238. Ku kiyaye salloli da kuma salla mafificiya, kuma ku tsaya domin Allah kuna masu nutsuwa.
239. To idan kuna cikin halin tsoro, sai ku yi salla kuna tafe da ƙafafuwanku ko a kan ababan hawanku. To idan kun amintu, sai ku ambaci Allah kamar yadda Ya sanar da ku abin da ba ku kasance kun sani ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da a kiyaye sallolin farilla gaba ɗayansu ta hanyar yin su a lokutansu da kula da rukunansu da sharuuɗansu, sannan ya ware sallar La'asar ita kaɗai, ya jaddada kula da ita.
An karɓo daga Aliyyu ɗan Abu Ɗalib (Allah ya kara masa yarda) ya ce: A ranar yaƙin gangami Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah ya cika musu gidajensu da ƙaburburansu da wuta, sun shagaltar da mu ba mu yi salla mafificiya ba har rana ta faɗi." [Bukhari #2931].
An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda sallar la'asar ta kuɓuce masa, to kamar ya yi asarar iyalansa ne da dukiyarsa." [Bukhari #552, da Muslim #626].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su tsaya a sallolinsu cikin nutsuwa ta zuciya da ta gaɓɓai, da barin wata maganar da ba ambaton Allah ba, ba kuma karatun Alƙur'ani ba.
To bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci masallata da tsayawa a sallar cikin nutsuwa da barin duk wata magana wadda ba ta danganci ambaton Allah da karatun Alƙur'ani ba, sai ya yi togaciyar hukuncin salla a lokacin da ake tsakiyar yaƙi a filin daga, ko lokacin faruwar wani abun tsoro. A irin wannan lokaci ma dole Musulmi sai sun yi salla, ba a ɗauke musu ita ba, sai dai idan suna jin tsoron ba za su iya yin ta ba kamar yadda ake yin ta a halin kwanciyar hankali, to su dai sallace ta a kowane irin yanayi suke ciki, suna tafe ne a kan ƙafafuwansu ko kuma a kan ababuwan hawansu ko suna kallon alƙibla ko ba sa kallon ta, ko ta halin ƙaƙa suka gudanar da ita, ta wadatar. To amma duk sa'adda wancan tsoro ya kau, wajibi ne su dawo su tsayar da salla kamar yadda aka koyar da su da farko, su yi ta cikakkiya. Domin ilimin da Allah ya koyar da su da hukunce-hukuncen da ba su san su ba a da, wannan wata babbar ni'ima ce a gare su da ya wajaba su yi wa Allah godiya a kanta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haƙƙin iyaye ne da waliyyan mata su hana 'ya'yansu aikata abin da ya saɓa wa shari'a wajen fita ko sutura ko mu'amala.

2. Taƙawa ce takan sa mutum ya kyautata wa matar da ya yi niyyar sakin ta.

3. Karfafa batun haƙƙoƙin mutane don kada a riƙa sakaci a kansu.

4. Rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa da yi musu bayanin hukunce-hukuncensa don rayuwarsu ta duniya da ta lahira ta yi kyau.

5. Sanin hukunce-hukuncen shari'a alama ce ta cikar hankali.

Suratul Baƙara (240-242)
وَٱلَّذِينَ يُتَوَفَّوْنَ مِنكُمْ وَيَذَرُونَ أَزْوَٰجًا وَصِيَّةً لِّأَزْوَٰجِهِم مَّتَٰعًا إِلَى ٱلْحَوْلِ غَيْرَ إِخْرَاجٍ ۚ فَإِنْ خَرَجْنَ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ فِى مَا فَعَلْنَ فِىٓ أَنفُسِهِنَّ مِن مَّعْرُوفٍ ۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٢٤٠﴾ وَلِلْمُطَلَّقَٰتِ مَتَٰعٌۢ بِٱلْمَعْرُوفِ ۖ حَقًّا عَلَى ٱلْمُتَّقِينَ ﴿٢٤١﴾ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿٢٤٢﴾

240. Kuma waɗanda suke rasuwa daga cikinku suke barin matan aure, (to za su yi) wasiyya ga matansu cewa, a jiyar da su daɗi har zuwa shekara, ba tare da an fitar da su ba; to idan su suka fita da kansu, to babu laifi a kanku dangane da abin da suka aikata wa kansu na abin da yake sananne a shari'a. Kuma Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.

241. Kuma matan da aka sake su suna da wata kyauta ta kwantar da hankali ta hanyar da aka saba, (wannan) haƙƙi ne a kan masu taƙawa.

242. Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyinsa don ku hankalta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da cewa, wajibi ne ga mazaje idan sun zo mutuwa, su bar wa magadansu wasiyyar cewa, matansu na aure su zauna a gidajen mazajen nasu masu rasuwa har tsawon shekara guda cikakkiya, sannan a kula da cinsu da shansu, ba tare da an fitar da su daga gidajen ba. Amma babu wani laifi a kan waliyyan mamaci, idan su matan suka fita daga gidajen bayan sun kammala takabarsu wata huɗu da kwana goma, suka yi kwalliya, suka sanya turare, suka nemi wani auren, da abin da ya yi kama da haka, wanda bai fita daga iyakokin shari'a da al'ada ba. Allah mabuwayi ne, babu mai iya hana shi yin uƙubarsa ga duk wanda ya saɓa wa umarninsa, ya aikata abin da ya hana, kuma mai hikima ne, duk wani hukunci da ya shar'anta cike yake da hikima da dacewa.
Yawancin malamai na farko da na baya-baya suna ganin wannan aya an shafe hukuncinta da aya ta 234 wadda ta gabata, inda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta wa matar da mijinta ya rasu ta yi masa takaba ta tsawon wata huɗu da kwana goma (idan kuma mai ciki ce, to za ta zauna tsawon lokacin da za ta haihu, da zarar ta haihu, to ta fita daga takaba). Waɗannan malamai sun ɗauki zamanta a gidan mijinta mai rasuwa tsawon shekara ɗaya, kamar yadda ya zo a wannan ayar zama ne na takaba, don haka suka ce, wannan hukunci an shafe shi da ayar da ta gabata wadda ta bayyana cewa, takabar miji wata huɗu ce da kwana goma kawai.
Amma wasu daga cikin malamai na tabi'ai da wasu na baya-baya suna ganin ayar tana umarni ne ga mazaje idan sun zo mutuwa, to su yi wasiyya ga magadansu a kan su ƙale matansu su zauna a gidajensu tsawon shekara ɗaya, kada su fitar da su, sai idan su ne suka zaɓi su fita. Wannan kuwa ya kasance ne kafin Allah ya shar'anta rabon gado, a inda ya ambaci kason mace daga dukiyar mijinta.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta wa maza su ba wa matan da suka saki wani abin tagomashi na dukiya ko tufafi gwargwadon yadda ya dace, ba tare da takurawa ba. Allah ya ƙarfafa hakan da cewa, wannan haƙƙi ne a kan masu taƙawa. To kamar yadda a baya Allah ya bayyana hukunce-hukuncen shari'arsa filla-filla, hakanan yake ci gaba da bayanin sauran ayoyin nasa da hukunce-hukuncensa dalla-dalla, don mutane su fahinta, su yi aiki da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayan da Allah ya yi wa muminai umarnin fita yaƙi don Allah, sai ya kawo musu abin da zai tabbatar musu da cewa, ba su ne al'umma ta farko da Allah ya umarta da fita yaƙi ba, Allah ya shar'anta yaƙi don kare addininsa a cikin wasu al'ummomin da suka gabace su kamar Banu Isra'ila. Hakan zai sa su sami ƙwarin gwiwar karɓar wannan umarni daga Allah, kuma su fahimci nasarar Allah da ke tattare da hakan.

2. Tsoro ba ya canza ƙaddara, kuma ba ya tsare rayuwa, rayuwa a hannun Allah take; yana ba da ita kyauta ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, ba tare da wani ƙoƙari nasu ba.

3. Kwaɗaitarwa a kan ciyarwa don Allah, kuma Allah yana ninka wa wanda duk ya bayar domin shi.

4. Muddin dai rayuwa da mutuwa a hannun Allah suke, yaƙi ba shi ne ke sa mutum ya rasa ransa ba, sai ajalinsa ya zo. Kuma bayar da dukiya don Allah ba shi ne zai sa dukiya ta ƙare ba, a'a, wannan kyakkyawan rance ne bawa ya ba wa Ubangijinsa, don haka ya kwantar da hankalinsa, Allah zai ba shi ninkin abin da ya bayar.

5. Wani lokaci mutum zai zaci cewa zai iya haƙuri ya bar abin da aka haramta masa, ko zai iya jurewa ya aikata abin da aka umarce shi da aikatawa, to sai an jarrabe shi da haka sai ka ga ya noƙe, ya ja da baya.

6. Duk wanda ya koma ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da gaske har zuciyarsa, to babu makawa Allah zai amsa masa addu'arsa.

7. Ɗabi'a ce ta kowace al'umma a riƙa samun saɓani wajen naɗa shugaba, wanda irin haka yakan haifar da rarrabuwar kai. To idan irin haka ya faru, dole ne a samu wani wanda zai raba gardama a tsakaninsu, waɗannan kuwa su ne malamai masu tsoron Allah da sanin ya kamata. Wajibi ne idan sun zartar da wani hukunci al'ummar Musulmi su yarda da shi koda kuwa ya saɓa wa abin da suke zaton shi ne daidai. Domin su ne magadan annabawa.

8. Haɗuwar shugabannin al'umma masu faɗa a ji, su tattauna al'amarin da ya shafi wannan al'ummar, su kai ga samun matsaya ɗaya a tsakaninsu, yana daga cikin manya-manyan dalilan cin nasarar wannan al'ummar da samun biyan buƙata cikin dukkan al'amuranta.

9. Samun siffar ilimi da kuma ƙarfin jiki da lafiyarsa, yana daga cikin siffofin shugaba da ake so, idan aka sami tawayar ɗaya daga cikin waɗannan siffofi biyu, to za a samu cikas a shugabancin wannan shugaba.

10. Yana daga cikin hikimar Allah, bambance tsakanin mai gaskiya da marar gaskiya da mai kirki da marar kirki da mai haƙuri da marar haƙuri. Kuma Allah ba zai taɓa ƙyale bayinsa hakanan a gauraye ba, ba tare da ya yi irin wannan tankaɗe da rairaya ba.

11. Biyayyar sojoji ga shugabansu a duk abin da zai ba su umarni da shi ko ya hana su muddun bai saɓa wa shari'a ba, yana daga cikin dalilai na samun nasara a fagen yaƙi.

12. Imani da Allah da Manzonsa da tsayawa a kan gaskiya, yana daga cikin dalilan samun nasara.

13. Kaɗan ne daga cikin mutane kan iya haƙuri a kan wata jarraba.14. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan ba da mulki ga wanda ma bai sa rai ba.

Suratul Baƙara (243-252)

* أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ خَرَجُواْ مِن دِيَٰرِهِمْ وَهُمْ أُلُوفٌ حَذَرَ ٱلْمَوْتِ فَقَالَ لَهُمُ ٱللَّهُ مُوتُواْ ثُمَّ أَحْيَٰهُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشْكُرُونَ ﴿٢٤٣﴾ وَقَٰتِلُواْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٤٤﴾ مَّن ذَا ٱلَّذِى يُقْرِضُ ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا فَيُضَٰعِفَهُۥ لَهُۥٓ أَضْعَافًا كَثِيرَةً ۚ وَٱللَّهُ يَقْبِضُ وَيَبْصُۜطُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٢٤٥﴾ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلْمَلَإِ مِنۢ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ مِنۢ بَعْدِ مُوسَىٰ إِذْ قَالُواْ لِنَبِىٍّ لَّهُمُ ٱبْعَثْ لَنَا مَلِكًا نُّقَٰتِلْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ ۖ قَالَ هَلْ عَسَيْتُمْ إِن كُتِبَ عَلَيْكُمُ ٱلْقِتَالُ أَلَّا تُقَٰتِلُواْ ۖ قَالُواْ وَمَا لَنَآ أَلَّا نُقَٰتِلَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَقَدْ أُخْرِجْنَا مِن دِيَٰرِنَا وَأَبْنَآئِنَا ۖ فَلَمَّا كُتِبَ عَلَيْهِمُ ٱلْقِتَالُ تَوَلَّوْاْ إِلَّا قَلِيلًا مِّنْهُمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٢٤٦﴾ وَقَالَ لَهُمْ نَبِيُّهُمْ إِنَّ ٱللَّهَ قَدْ بَعَثَ لَكُمْ طَالُوتَ مَلِكًا ۚ قَالُوٓاْ أَنَّىٰ يَكُونُ لَهُ ٱلْمُلْكُ عَلَيْنَا وَنَحْنُ أَحَقُّ بِٱلْمُلْكِ مِنْهُ وَلَمْ يُؤْتَ سَعَةً مِّنَ ٱلْمَالِ ۚ قَالَ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصْطَفَىٰهُ عَلَيْكُمْ وَزَادَهُۥ بَسْطَةً فِى

ٱلۡعِلۡمِ وَٱلۡجِسۡمِۖ وَٱللَّهُ يُؤۡتِي مُلۡكَهُۥ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ ٢٤٧ وَقَالَ لَهُمۡ نَبِيُّهُمۡ إِنَّ ءَايَةَ مُلۡكِهِۦٓ أَن يَأۡتِيَكُمُ ٱلتَّابُوتُ فِيهِ سَكِينَةٞ مِّن رَّبِّكُمۡ وَبَقِيَّةٞ مِّمَّا تَرَكَ ءَالُ مُوسَىٰ وَءَالُ هَٰرُونَ تَحۡمِلُهُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لَّكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٢٤٨ فَلَمَّا فَصَلَ طَالُوتُ بِٱلۡجُنُودِ قَالَ إِنَّ ٱللَّهَ مُبۡتَلِيكُم بِنَهَرٖ فَمَن شَرِبَ مِنۡهُ فَلَيۡسَ مِنِّي وَمَن لَّمۡ يَطۡعَمۡهُ فَإِنَّهُۥ مِنِّيٓ إِلَّا مَنِ ٱغۡتَرَفَ غُرۡفَةَۢ بِيَدِهِۦۚ فَشَرِبُواْ مِنۡهُ إِلَّا قَلِيلٗا مِّنۡهُمۡۗ فَلَمَّا جَاوَزَهُۥ هُوَ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ قَالُواْ لَا طَاقَةَ لَنَا ٱلۡيَوۡمَ بِجَالُوتَ وَجُنُودِهِۦۚ قَالَ ٱلَّذِينَ يَظُنُّونَ أَنَّهُم مُّلَٰقُواْ ٱللَّهِ كَم مِّن فِئَةٖ قَلِيلَةٍ غَلَبَتۡ فِئَةَۢ كَثِيرَةَۢ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٢٤٩ وَلَمَّا بَرَزُواْ لِجَالُوتَ وَجُنُودِهِۦ قَالُواْ رَبَّنَآ أَفۡرِغۡ عَلَيۡنَا صَبۡرٗا وَثَبِّتۡ أَقۡدَامَنَا وَٱنصُرۡنَا عَلَى ٱلۡقَوۡمِ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٢٥٠ فَهَزَمُوهُم بِإِذۡنِ ٱللَّهِ وَقَتَلَ دَاوُۥدُ جَالُوتَ وَءَاتَىٰهُ ٱللَّهُ ٱلۡمُلۡكَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَعَلَّمَهُۥ مِمَّا يَشَآءُۗ وَلَوۡلَا دَفۡعُ ٱللَّهِ ٱلنَّاسَ بَعۡضَهُم بِبَعۡضٖ لَّفَسَدَتِ ٱلۡأَرۡضُ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ ذُو فَضۡلٍ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢٥١ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ نَتۡلُوهَا عَلَيۡكَ بِٱلۡحَقِّۚ وَإِنَّكَ لَمِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٢٥٢

243. Shin ba ka ga waɗanda suka fita daga gidajensu ba su dubbai don tsoron mutuwa, sai Allah Ya ce da su: “Ku mutu”, sannan Ya raya su? Lalle Allah Ma’abocin falala ne ga mutane, sai dai yawancin mutane ba sa godiya.

244. Kuma ku yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah, kuma ku sani cewa, lalle Allah Mai ji ne, Masani.

245. Wane ne zai ba wa Allah kyakkyawan rance, sai Ya ninka masa shi ninki mai yawa? Kuma Allah ne Yake kame (dukiya), Yake kuma shimfiɗa ta, kuma zuwa gare Shi za a mayar da ku.

246. Shin ba ka ga wasu manyan mutane ba daga cikin Banu Isra’ila bayan (mutuwar) Musa yayin da suka faɗa wa Annabinsu: “Ka naɗa mana wani sarki, wanda za mu yi yaƙi (tare da shi) don ɗaukaka kalmar Allah?” Sai ya ce: “Shin ba kwa tsammanin idan an wajabta muku yaƙi, ba za ku yi yaƙin ba?” Sai suka ce: “Me zai sa ba za mu yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah ba, alhali kuwa an fitar da mu daga gidajenmu da ‘ya’yanmu?” To yayin da aka wajabta musu yaƙin sai suka juya baya sai ‘yan kaɗan daga cikinsu. Kuma Allah Masanin azzalumai ne.

247. Kuma Annabinsu ya ce da su: “Lalle haƙiƙa Allah Ya naɗa Ɗalutu ya zama Sarki gare ku.” Sai suka ce: “Ta yaya zai samu sarauta a kanmu, alhalin mun fi shi cancatar sarauta, kuma ba a ba shi yalwar dukiya ba?” Sai ya ce: “Lalle Allah Ya zaɓe shi a kanku, kuma Ya ƙara shi da yalwar ilimi da ta girman jiki, kuma Allah Yana bayar da mulkinsa ga wanda Ya ga dama, kuma Allah Mai yalwa ne, Masani.”

248. Sai Annabinsu ya ce da su: “Lalle alamar (cancantar) mulkinsa ita ce akwatin nan da zai zo muku wanda a cikinsa akwai nutsuwa daga Ubangijinku da kuma sauran abin da iyalin Musa suka bari da iyalin Haruna; mala’iku na ɗauke da shi. Lalle a cikin wannan tabbas akwai aya a gare ku, in kun kasance muminai.”

249. To yayin da Ɗalutu ya fita (bayan gari) da rundunarsa, sai ya ce: “Lalle Allah zai jarrabe ku da wata ƙorama, to duk wanda ya sha daga gare ta, to ba ya tare da ni, duk wanda kuwa bai sha ba, to wannan yana tare da ni, sai dai wanda ya kamfata sau ɗaya da (tafin) hannunsa.” Gaba ɗayansu sai suka sha daga cikinta sai ‘yan kaɗan daga cikinsu (su ne ba su sha ba). To yayin da ya ƙetare shi, shi da waɗanda suka yi imani tare da shi, sai suka ce: “A yau kam ba mu da iko wajen fuskantar Jalutu da rundunarsa.” Sai

waɗanda suke da yaƙinin cewa za su haɗu da Allah suka ce: “Sau da yawa wata runduna ‘yan kaɗan takan yi rinjaye a kan wata runduna mai yawa da izinin Allah. Kuma Allah Yana tare da masu haƙuri.”

250. Kuma yayin da suka yi fito-na-fito da Jalutu da rundunarsa, sai suka ce: “Ya Ubangijinmu, Ka zubo mana haƙuri na musamman, kuma Ka tabbatar da dugaduganmu, kuma Ka taimake mu a kan mutane kafirai.”

251. Sai suka murƙushe su da izinin Allah, kuma Dawudu ya kashe Jalutu, sai Allah Ya ba shi mulki da hikima, kuma Ya sanar da shi irin abin da Ya ga dama. Ba don yadda Allah Yake kare wani sashin mutane da wani sashi ba, to lalle da ƙasa ta lalace, sai dai kuma Allah Ma’abocin falala ne ga talikai.

252. Waɗannan ayoyin Allah ne, Muna karanta maka su da gaskiya, kuma lalle kai tabbas kana cikin manzanni.

A waɗannan ayoyi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba mu labarin waɗansu dubban jama’a, waɗanda suka gudu daga gidajensu don tsoron mutuwa, ko dai saboda wata annoba da ta ɓarke a garin ko kuma saboda abokan gabansu da suka auka musu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kashe su gaba ɗayansu, sannan ya sake raya su bayan wani ɗan lokaci, don su fahimci cewa, babu wanda zai iya guje wa mutuwa idan ajalinsa ya zo. Allah ya sake tayar da su ne don ya nuna musu irin falalarsa mai yawa ga halittunsa, sai dai kuma da dama daga cikin mutane ba sa nuna godiya ga ni’imar da Allah ya yi musu.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa muminai da su fito su yi jihadi don ɗaukaka kalmar Allah, da ba da kariya ga addininsu da al’ummarsu, su sani kuma Allah yana jin duk maganganunsu, yana sane da duk wani hali da suke ciki, don haka su guji saɓa wa umarninsa.
To kasancewar jihadi ba zai yiwu ba sai an fitar da dukiya, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar bisa ciyarwa domin shi, ya yi alƙawarin gwaggwaɓan sakamako ga duk wanda ya ba da dukiyarsa saboda Allah da cewa, zai ninka masa ita ninki mai yawa. Kuma saboda ma kar wani ya yi zaton cewa, fitar da dukiya da bayar da ita don Allah zai jawo masa talauci, sai Allah ya bayyana masa cewa, komai yana hannunsa, shi ne wanda yake yalwata wa wanda ya ga dama yake kuma ƙuntata wa wanda ya ga damar ya ƙuntata masa. Kuma kowa makomarsa zuwa ga Allah take ranar gobe ƙiyama, don ya yi wa kowa sakamako a kan aikinsa da ya aikata.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin wasu mutane daga cikin Banu Isra’ila, bayan rasuwar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), lokacin da dattawa da masu faɗa a ji daga cikinsu suka yi taro, suka nemi wani annabi daga cikinsu da ya naɗa musu shugaba wanda zai jagorance su, su yi yaƙi a ƙarƙashin tutarsa. Sai wannan Annabi ya tambaye su cewa, shin suna zaton idan Allah ya wajabta musu yaƙi, za su tsaya su yi yaƙin? Sai suka amsa masa da cewa, babu abin da zai hana su yin yaƙi don Allah, musamman ma bayan maƙiyansu sun kore su daga gidajensu, sun raba su da ‘ya’yansu, bayan sun kama su sun mayar da su bayi. To bayan Allah ya wajabta musu yaƙin, sai ga shi da yawa daga cikinsu sun noƙe, sun ƙi fita, sai ‘yan kaɗan ne suka cika alƙawarin da suka ɗauka. Allah ya san azzalumi daga cikinsu, mai saba alƙawari, kuma zai yi masa sakamako a kan zaluncinsa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin yadda labarin waɗannan mutane ya kasance. Annabinsu ya sanar da su cewa, Allah ya karɓi buƙatarsu, ya naɗa musu Ɗaluta da ya zama Sarkinsu, wanda zai zama jagoransu a wannan yaƙin. Ɗaluta mutum ne daga cikin talakawan Banu Isra’ila, ba shi da dangantaka da gidan sarautarsu, don haka sai suka nuna rashin gamsuwarsu da wannan zaɓi da aka yi wa Ɗaluta. Suka ce, ta yaya zai zama sarkinsu, alhali bai fi su da komai ba, hasali ma su suka fi shi cancantar sarautar, sannan ga shi ba mai dukiya ba, ballantana a sallama masa saboda yawan dukiyarsa. Sai wannan Annabin nasu ya mayar musu da jawabi, da cewa, wannan bawan Allah, Allah ne ya zaɓe shi ya ba shi wannan sarautar, ya kuma ba shi ilimi mai yawa, ga shi kuma da tsawo da ƙarfi da Allah ya hore masa. Kuma ai mulki duka na Allah ne shi kaɗai, yana ba da shi ga wanda ya ga dama, daga kowane irin

rukuni na al'umma ya fito, ba lalle sai ya zama ɗan gidan sarauta ba, kuma ba lalle ne ya zama mai dukiya ba, domin falalar Allah mayalwaciya ce, ba wanda ba za ta iya shafa ba, Allah kuma mai cikakken sani ne game da komai, shi ya san wanda ya kamata ya ba wa mulki.
Wannan Annabin kuma ya ci gaba da yi musu bayani game da wannan zaɓi da Allah ya yi wa Ɗaluta na sarauta. Ya ce musu, alamar ingancin naɗinsa a matsayin Sarkinsu, shi ne za a dawo musu da akwatinsu da aka taɓa ɗauke musu, wanda yin haka zai haifar musu da nutsuwa a zukatansu, sannan kuma abin da yake cikin akwatin yana ƙunshe da abin da zai kwantar musu da hankali; har ila yau a cikinsa akwai sauran kayan gado, wanda iyalan Annabi Musa da Annabi Haruna suka bari, kuma mala'iku ne za su ɗauko wannan akwatin su kawo shi. Tabbas wannan alama ce ta fili da za ta tabbatar musu gaskiyar zaɓin da Allah ya yi wa Ɗaluta a matsayin Sarkinsu, in dai har sun kasance muminai, sun ba da gaskiya da Allah, to za su gaskata labarin da ya ba su a matsayinsa na Annabinsu.
To bayan da suka gamsu da naɗin Ɗaluta a matsayin Sarki wanda zai jagorance su su yaƙi abokan gabarsu, sai duk suka zama sojoji a ƙarƙashin tutarsa, ya kuma fita da su. Bayan sun bar garinsu, sai ya faɗa musu cewa, akwai wata ƙorama da za su ci karo da ita a hanya; wannan ƙorama jarabawa ce a gare su; idan sun iske ta, to duk irin ƙishin da suke ji, kada wanda ya sha ruwanta fiye da kamfatar cikin hannunsa ɗaya. Allah ya yi musu haka ne don ya tantance masu gaskiya daga cikinsu da kuma maƙaryatan cikinsu, a gane masu juriya da waɗanda ba su da juriya. Ɗaluta ya faɗa musu ƙarara cewa, duk wanda ya saɓa wa wannan dokar, ya kwankwaɗi ruwan wannan ƙoramar, to ba ya tare da shi. To suna zuwa wurin wannan ƙoramar kuwa, sai yawancinsu suka sha wannan ruwan, sai 'yan kaɗan ne ba su sha ba, ko waɗanda ba su wuce kamfata ɗaya ba. Wannan ya sa sojojin Ɗaluta suka koma 'yan kaɗan.
To lokacin da Ɗaluta ya tsallaka wannan ƙoramar, shi da sojojinsa 'yan kaɗan masu imani suka hango yawan sojojin abokan gabarsu, sai wasu daga cikinsu suka fara cewa, yau kam ba za mu iya fuskantar Jaluta da rundunarsa ba, saboda yawansu da yawan makamansu. To a nan ne masu ƙarfin imani da yaƙinin za su koma ga Allah suka ce, sau da yawa wata runduna 'yar kaɗan takan yi rinjaye a kan wata runduna mai yawa da ikon Allah, don haka duk wanda Allah ya watsar da shi, yawansa ba zai amfana masa komai ba, hakanan wanda Allah ya yake tare da shi, rashin yawansa ba zai cutar da shi da komai ba, Allah kuma yana tare da masu haƙuri a kan yi masa biyayya da juriya a kan komai.
To bayan rundunar Sarki Ɗaluta da rundunar Jaluta sun yi gaba-da-gaba da juna, sai muminai suka roƙi Ubangijinsu da ya kimsa musu haƙuri, ya ba su jajircewa, kada yawan abokan gabarsu ya sa su ji tsoro su gudu, kuma ya ba su nasara a kan kafirai. Sai ko Allah ya karɓi addu'arsu, ya ba su galaba, suka murƙushe mayaƙan Jaluta, kuma Allah ya ɗora Dawudu a kan Jaluta, ya kashe shi a filin daga, a dalilin haka Allah ya yi wa Dawudu kyautar mulki da ta annabta, ya sanar da shi ilimin da ya ga dama, kamar sanin fannin ƙira da sarrafa ƙarfe yadda yake so, kamar yadda Allah ya ambata a *Suratul Anbiya'i*, aya ta 80.
Ba don Allah yana kare muminai daga makircin kafirai ta hanyar muminai masu jihadi ba, to da ɓarna ta yaɗu a bayan ƙasa, sai dai Allah mai yalwar falala ne a kan dukkan halittunsa, don haka ne ya shar'anta musu yin jihadi, domin su tashi su kare kansu, kuma su hana ɓarna yaɗuwa a bayan ƙasa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, duk waɗannan labarai da yake ba shi, na al'ummomin da suka gabata, na gaskiya ne, kuma sun yi daidai da abin da yake cikin littattafan manzannin da suka gabace shi. Waɗannan kuma alamomi ne da hujjoji masu tabbatar da cewa, shi Annabin Allah ne, kuma abin da yake karanta musu daga Allah yake, don haka Allah ya sake tabbatar masa da cewa, "Lalle kai kana cikin manzanni."

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawa da manzanni mabambanta ne wajen daraja, wasu sun fi wasu daraja.

2. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba Allah ba ne, don haka ya buƙaci Allah ya ƙarfafe shi da Mala'ika Jibrilu, da kuwa shi Allah ne, da bai buƙaci haka ba.

3. Saɓani a kan gaskiya da rarrabar mutane a kanta, shi ne yake haifar da yaƙe-yaƙe a junansu.

Suratul Baƙara (253)

۞ تِلْكَ ٱلرُّسُلُ فَضَّلْنَا بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ ۘ مِّنْهُم مَّن كَلَّمَ ٱللَّهُ ۖ وَرَفَعَ بَعْضَهُمْ دَرَجَٰتٍ ۚ وَءَاتَيْنَا عِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ٱلْبَيِّنَٰتِ وَأَيَّدْنَٰهُ بِرُوحِ ٱلْقُدُسِ ۗ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقْتَتَلَ ٱلَّذِينَ مِنۢ بَعْدِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا جَآءَتْهُمُ ٱلْبَيِّنَٰتُ وَلَٰكِنِ ٱخْتَلَفُوا۟ فَمِنْهُم مَّنْ ءَامَنَ وَمِنْهُم مَّن كَفَرَ ۚ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَا ٱقْتَتَلُوا۟ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَفْعَلُ مَا يُرِيدُ ﴿٢٥٣﴾

253. Waɗannan manzanni, Mun fifita sashinsu a kan sashi. Cikinsu akwai wanda Allah Ya yi magana da shi, kuma Ya ɗaukaka wasunsu da darajoji. Kuma Mun bai wa Isa ɗan Maryam hujjoji bayyanannu, kuma Mun ƙarfafe shi da Ruhi mai tsarki. Da kuma Allah Ya ga dama da waɗanda suka zo bayansu ba su yaƙi juna ba bayan hujjoji bayanannu sun zo musu, sai dai kuma sun yi saɓani; cikinsu akwai wanda ya yi imani, kuma cikinsu akwai wanda ya kafirce, kuma da Allah Ya ga dama da ba su yaƙi juna ba, sai dai Allah Yana aikata abin da Yake nufi.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tabbatar da cewa, manzanninsa masu matsayi da daraja ne a wurinsa, darajojinsu da matsayinsu sun bambanta; wasu sun ɗara wasu daraja. Daga cikinsu akwai wanda Allah ya yi magana da shi, kamar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), akwai kuma wanda Allah ya ɗaukaka shi da darajoji masu yawa, kamar Annabi Muhammad (ﷺ), ya fifita shi a kan sauran annabawa. Sannan kuma akwai Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), wanda Allah ya ba shi mu'ujizoji da yawa, masu tabbatar da gaskiyar annabcinsa, sannan ya ba shi littafin Injila, kamar yadda ya ƙarfafe shi da Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Da Allah ya nufa, da babu wasu da za su zo bayan aiko da wani manzo, su yi yaƙi a junansu bayan hujjoji masu bayyana haƙiƙanin gaskiya sun zo musu. Sai dai saɓanin da suka yi a kan waɗannan hujjojin bayyanannu shi ya haifar da yaƙi a tsakaninsu; wasu daga cikinsu suka yi imani, wasu kuma suka kafirce. Da Allah ya yi nufin ya haɗa kansu gaba ɗaya, ya hana su yaƙar junansu, da ya yi hakan, sai dai Allah yana aikata abin da ya ga dama ne, kuma duk abin da yake nufi shi ne yake wakana.

Daga wannan ayoyin za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani yana sa mai shi ya bayar da dukiyarsa don Allah; ƙarancin imani kuma yana haifar da rowa. Shi ya sa mai imani yake zama mai kyauta da dukiyarsa da iliminsa da matsayinsa da ƙarfin jikinsa.

2. Duk arzikin da bawa yake da shi daga Allah ne, don haka ba ya da abin da zai goranta wa Allah da shi don ya ciyar da dukiyarsa.

3. Ceto ba zai amfani kafiri ba a ranar alƙiyama.

4. Kafirci ne mafi girman zalunci, domin ya ƙunshi ɗaukar haƙƙin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a bai wa waninsa.

5. Tabbatar da ceto ga masu zunubi ranar alƙiyama, bayan Allah ya yi izini ga mai yin ceton, ya yarda da wanda za a ceta.

6. Allah shi ne yake tsare da sammai da ƙasa, ba don haka ba da tuni sun lalace.

7. Tabbatar da Kursiyyu ga Allah. An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Kursiyyu shi ne wurin dugadugai, Al-Arshi kuwa ba wanda ya san iya girmansa.” [Dubi Tafsir Abdurrazaƙ #3030, Ibn Khuzaima, *Attauhid* 1:249, Ibn Abi Hatim, Attafsir #260]. Imam Az-Zahbi da Albani duka sun inganta shi. [Dubi Al-Uluw #76, *Sharhut Tahawiyyah*, Shafi na 279].
8. Tabbatar da ɗaukakar Allah a kan duk halittunsa, ɗaukaka ta Zati, da ɗaukaka ta sifofi, da ɗaukaka ta iko.

9. Imanin bawa ba zai cika ba, har sai ya kafirce wa duk wani abu da ake bauta wa ba Allah ba, ya yi imani da Allah shi kaɗai.

10. Imani haske ne guda ɗaya, kafirci kuma duffai ne iri-iri.

Suratul Baƙara (254-257)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنفِقُواْ مِمَّا رَزَقْنَـٰكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِىَ يَوْمٌ لَّا بَيْعٌ فِيهِ وَلَا خُلَّةٌ وَلَا شَفَـٰعَةٌ ۗ وَٱلْكَـٰفِرُونَ هُمُ ٱلظَّـٰلِمُونَ ﴿٢٥٤﴾ ٱللَّهُ لَآ إِلَـٰهَ
إِلَّا هُوَ ٱلْحَىُّ ٱلْقَيُّومُ ۚ لَا تَأْخُذُهُۥ سِنَةٌ وَلَا نَوْمٌ ۚ لَّهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۗ مَن ذَا ٱلَّذِى يَشْفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذْنِهِۦ ۚ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ
وَمَا خَلْفَهُمْ ۖ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَىْءٍ مِّنْ عِلْمِهِۦٓ إِلَّا بِمَا شَآءَ ۚ وَسِعَ كُرْسِيُّهُ ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ ۖ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفْظُهُمَا ۚ وَهُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْعَظِيمُ ﴿٢٥٥﴾ لَآ
إِكْرَاهَ فِى ٱلدِّينِ ۖ قَد تَّبَيَّنَ ٱلرُّشْدُ مِنَ ٱلْغَىِّ ۚ فَمَن يَكْفُرْ بِٱلطَّـٰغُوتِ وَيُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱسْتَمْسَكَ بِٱلْعُرْوَةِ ٱلْوُثْقَىٰ لَا ٱنفِصَامَ لَهَا ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ
عَلِيمٌ ﴿٢٥٦﴾ ٱللَّهُ وَلِىُّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ يُخْرِجُهُم مِّنَ ٱلظُّلُمَـٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ ۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَوْلِيَآؤُهُمُ ٱلطَّـٰغُوتُ يُخْرِجُونَهُم مِّنَ ٱلنُّورِ إِلَى ٱلظُّلُمَـٰتِ ۗ
أُو۟لَـٰٓئِكَ أَصْحَـٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا خَـٰلِدُونَ ﴿٢٥٧﴾

254. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ciyar daga abin da Muka arzurta ku (da shi) tun kafin wani yini ya zo wanda babu ciniki a cikinsa kuma babu abokantaka, kuma babu ceto. Kafirai kuwa su ne azzalumai.

255. Allah, babu wani abin bauta wa da cancanta sai Shi, Rayayye, Tsayayye da Zatinsa; gyangyaɗi ba ya kama shi, ballantana barci. Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne shi kaɗai. Wane ne ya isa ya yi ceto a wurinsa in ba da izininsa ba? Ya san abin da yake tare da su a yanzu da kuma abin da zai biyo bayansu; kuma ba sa iya sanin wani abu cikin iliminsa sai abin da Ya ga dama. Kursiyyunsa ya yalwaci sammai da ƙasa, kuma kiyaye su ba zai nauyaye Shi ba, kuma Shi ne Maɗaukaki Mai girma.

256. Babu tilastawa a addini, haƙiƙa shiriya ta riga ta bayyana daban da ɓata. Don haka duk wanda ya kafirce wa Ɗagutu, kuma ya yi imani da Allah, to haƙiƙa ya yi riƙo da igiya mafi ƙarfi wadda ba ta tsinkewa. Kuma Allah Mai ji ne, Masani.

257. Allah Shi ne Majiɓincin lamarin waɗanda suka yi imani, Yana fitar da su daga duffai zuwa ga haske; waɗanda suka kafirce kuwa, majiɓinta lamarinsu su ne ɗagutai, suna fitar da su daga haske zuwa duffai. Waɗannan su ne ‘yan wuta; su masu dawwama ne a cikinta.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar bayinsa da su ciyar daga arzikin da Allah ya ba su, tun gabanin zuwan ranar alƙiyama, ranar da babu kasuwanci a cikinta, babu wani aboki da zai taimaka wa abokinsa, babu wanda zai ceci wani, a karɓi cetonsa, sai wanda Allah ya yi wa izinin ya yi ceto. Sannan Allah ya bayyana cewa, kafirai masu ƙaryata manzannin Allah da faɗa da gaskiya, su ne azzalumai. Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin siffofin Abin bauta na gaskiya, ba wanda waɗancan azzalumai suka ɗauka abin bauta ba, wato ba irin yadda Larabawa suka mayar da gumakansu

abubuwan bautawa, ba Allah ba, ba kuma irin yadda Yahudu da Nasara suke jingina wa Allah wasu siffofi waɗanda ba su dace da Abin bauta na gaskiya ba. Allah ya siffanta kansa da cewa, shi ne Abin bauta, wanda babu wani abin bauta na gaskiya in ba shi ba. Ya siffantu da cikakkiyar rayuwa, wadda rashi bai gabace ta ba, kuma gushewa ba za ta riske ta ba; shi ne Tsayayye da Zatinsa, ba shi da buƙata a wajen kowa, kowa da komai masu buƙata ne a wajensa. Rayuwarsa da tsayuwarsa da Zatinsa, su suka tabbatar da barci ba ya kama shi ko gyangyaɗi. Duk wani abu da ke cikin sammai da ƙasa nasa ne. Babu mai ikon ya yi ceto a gabansa, sai da izininsa. Ya san komai na bayinsa, wanda aka yi, da wanda za a yi a nan gaba; su kuma bayinsa babu abin da za su iya sani, sai ɗan abin da ya sanar da su bisa ganin damarsa. Saboda girmansa da buwayarsa, Kujerarsa ta yalwaci sammai da ƙasa duka, kuma faɗin sammai da ƙasa da girmansu, ba ya ba shi wata wahala wajen kula da su; kula da su da kiyaye su abu ne mai matuƙar sauƙi a wurinsa. Shi ne mai cikakkiyar ɗaukaka ta Zati, da ɗaukaka ta ƙarfi, da ɗaukaka ta siffofi, da ɗaukaka ta kowane ɓangare nasa, kamar yadda yake da cikakken girma a Zatinsa da siffofinsa.
Hadisai na Annabi (ﷺ) ingantattu sun zo da bayanin falalar Ayatul Kursiyyu, wato aya ta 255 da ta gabata.

Daga cikinsu akwai Hadisin Ubayyu ɗan Ka'ab, ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce mini: "Ya baban Munzir, shin ka san wacce aya ce a littafin Allah ta fi girma?" Ya ce, sai na ce: "Allah da Manzonsa ne suka fi sani." Sai ya ce: "Ya baban Munzir, shin ka san wacce aya ce a littafin Allah tare da kai ta fi girma?" Ya ce sai na ce: "Allah da Manzonsa ne mafi sani." Sannan sai Ubayyu ya ce, sai na ce: Ita ce, "Allah, babu abin bauta wa da gaskiya sai shi, Rayayye, Tsayayye da Zatinsa...." Sai ya bugi ƙirjina, ya ce: "Na rantse da Allah, ina maka murna da samun wannan ilimi, ya baban Munzir." [Muslim #810].

Hakanan ya zo a hadisin Abu Hurairata (Allah ya kara masa yarda) cewa, Shaiɗan ya faɗa masa cewa, idan zai riƙa karanta Ayatul Kursiyyu har ƙarshenta, lokacin da ya zo kwanciya a shimfiɗarsa, to Allah zai sanya masa tsaronsa, kuma Shaiɗan ba zai iya matsawa kusa da shi ba har gari ya waye. Abu Hurairata ya je ya faɗa wa Annabi (ﷺ) wannan batu na Shaiɗan, Annabi (ﷺ) ya ce masa: "Ya faɗa maka gaskiya, duk kuwa da cewa shi babban mƙaryaci ne." [Bukhari #2311].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi bayanin cewa, babu tilastawa a addini, don haka bai dace a tilasta wani sai ya zama Musulmi ba; shi addinin Musulunci a bayyane yake, ya sha bamban da duk wata hanyar ɓata, dalilan ingancinsa a fili suke ƙarara, don haka duk wanda zai shige shi, ya shige shi ne bayan ya gamsu da gaskiyarsa har zuciyarsa. Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da bayani cewa, duk wanda ya kafirce wa Ɗagutu, wato duk wani abin bauta da bawa zai wuce iyaka da shi, ko abin bi ko abin yi wa ɗa'a, to duk wanda ya kafirce wa wannan, ya yi imani da Allah shi kaɗai, shi kam ya yi riƙo da addinin gaskiya. Allah yana jin duk wanda ya bayyana kafircewarsa ga Ɗagutu da imaninsa da Allah da wanda ba haka yake ba, ya san abin da kowa daga cikinsu ya ɓoye a zuciyarsa, kuma zai yi wa kowa sakamako gwargwadon aikinsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya zama mumini na gaskiya, to Allah mai jiɓintar lamarinsa ne a ko da yaushe, ya zamo mai taimakon sa, mai agajin sa, zai kuma tsame shi daga duhun ɓata zuwa hasken shiriya, daga duhun kafirci zuwa hasken imani, daga duhun munafunci zuwa ga hasken ikhlasi, daga duhun saɓon Allah zuwa ga hasken ɗa'a ga Allah, daga duhun bidi'a zuwa ga hasken sunna. Amma kafirai ba su da masu jiɓintar al'amuransu sai Ɗagutu, wanda shi ne abokin tafiyarsu. Babban Ɗagutu kuwa shi ne Shaiɗan la'ananne, shi ne zai riƙa fitar da su daga haske zuwa duffai na shirka da ɓata da saɓon Allah, kuma waɗannan su ne masu shiga wuta, su dawwama a cikinta ta har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ni'ima idan ta kasance ga wanda bai san Allah ba, za ta iya kai shi ga halaka, don za ta haifar masa da girman kai da raina masu faɗa masa gaskiya.

2. Yana daga cikin dangin zalunci, mutum ya san gaskiya, amma ya riƙa jayayya a kai, yana musu.

3. Duk sa'adda mutum ya ƙara siffantuwa da zalunci, to shiriyar Allah tana ƙara nisa da shi, kamar yadda duk sa'adda ya siffantu da adalci, to yana ƙara kusantar shiriyar Allah.

4. Mulkin duk wani mai mulki, ba nasa ba ne, na Allah ne, riƙo kaɗai aka ba shi.

5. Kudurar Allah ta wuce abin da mutane suka saba gani. Ka dubi yadda abinci da abin sha suka shekara ɗari ajiye, amma ba su lalace ba.

6. Karamar waliyyai gaskiya ce, ita ce Allah ya gudanar da wani abu da ba a saba gani ba a hannun wani mumini mai taƙawa don girmama shi ko ba shi kariya ko tabbatar da shari'a ta hannunsa. Duk wata karama ga wani waliyyi, to mu'ujiza ce ga annabin da yake yi wa biyayya.

7. Babu laifi mumini ya roƙi Allah ya nuna masa abin da zai ƙara haɓaka masa imaninsa.

Suratul Baƙara (258-260)

أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِي حَآجَّ إِبۡرَٰهِـۧمَ فِي رَبِّهِۦٓ أَنۡ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُ ٱلۡمُلۡكَ إِذۡ قَالَ إِبۡرَٰهِـۧمُ رَبِّيَ ٱلَّذِي يُحۡيِۦ وَيُمِيتُ قَالَ أَنَا۠ أُحۡيِۦ وَأُمِيتُۖ قَالَ إِبۡرَٰهِـۧمُ فَإِنَّ ٱللَّهَ يَأۡتِي بِٱلشَّمۡسِ مِنَ ٱلۡمَشۡرِقِ فَأۡتِ بِهَا مِنَ ٱلۡمَغۡرِبِ فَبُهِتَ ٱلَّذِي كَفَرَۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٥٨ أَوۡ كَٱلَّذِي مَرَّ عَلَىٰ قَرۡيَةٖ وَهِيَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا قَالَ أَنَّىٰ يُحۡيِۦ هَٰذِهِ ٱللَّهُ بَعۡدَ مَوۡتِهَاۖ فَأَمَاتَهُ ٱللَّهُ مِاْئَةَ عَامٖ ثُمَّ بَعَثَهُۥۖ قَالَ كَمۡ لَبِثۡتَۖ قَالَ لَبِثۡتُ يَوۡمًا أَوۡ بَعۡضَ يَوۡمٖۖ قَالَ بَل لَّبِثۡتَ مِاْئَةَ عَامٖ فَٱنظُرۡ إِلَىٰ طَعَامِكَ وَشَرَابِكَ لَمۡ يَتَسَنَّهۡۖ وَٱنظُرۡ إِلَىٰ حِمَارِكَ وَلِنَجۡعَلَكَ ءَايَةٗ لِّلنَّاسِۖ وَٱنظُرۡ إِلَى ٱلۡعِظَامِ كَيۡفَ نُنشِزُهَا ثُمَّ نَكۡسُوهَا لَحۡمٗاۚ فَلَمَّا تَبَيَّنَ لَهُۥ قَالَ أَعۡلَمُ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٥٩ وَإِذۡ قَالَ إِبۡرَٰهِـۧمُ رَبِّ أَرِنِي كَيۡفَ تُحۡيِ ٱلۡمَوۡتَىٰۖ قَالَ أَوَلَمۡ تُؤۡمِنۖ قَالَ بَلَىٰ وَلَٰكِن لِّيَطۡمَئِنَّ قَلۡبِيۖ قَالَ فَخُذۡ أَرۡبَعَةٗ مِّنَ ٱلطَّيۡرِ فَصُرۡهُنَّ إِلَيۡكَ ثُمَّ ٱجۡعَلۡ عَلَىٰ كُلِّ جَبَلٖ مِّنۡهُنَّ جُزۡءٗا ثُمَّ ٱدۡعُهُنَّ يَأۡتِينَكَ سَعۡيٗاۚ وَٱعۡلَمۡ أَنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٢٦٠

258. Shin ba ka ga wanda ya yi jayayya da Ibrahim ba game da lamarin Ubangijinsa, don Allah ya ba shi mulki, yayin da Ibrahimu ya ce: "Ubangijina Shi ne Yake rayawa, kuma Yake kashewa." Sai ya ce: "Ai ni ma ina rayawa, kuma ina kashewa." Sai Ibrahim ya ce: "To Allah Yana zuwa da rana daga gabas, to kai ka zo da ita daga yamma." Sai wanda ya kafirta ya kiɗime. Kuma Allah ba Ya shiryar da mutanen da suke azzalumai.

259. Ko kuma kamar mutumin da ya wuce ta wata alƙarya alhalin ta zama kango, sai ya ce: "Ta yaya Allah zai raya wannan bayan mutuwarta?" Sai Allah Ya karɓi rayuwarsa tsawon shekara ɗari, sannan Ya tashe shi, Ya ce: "Mene ne tsawon lokacin da ka zauna?" Sai ya ce: "Ai na zauna yini ɗaya ne ko ma wani sashi na yinin." Sai Ya ce: "Ai ka zauna tsawon shekara ɗari ne, don haka dubi abincinka da abin shanka bai canja ba, kuma ka dubi jakinka mana ka gani, don Mu sanya ka ka zamanto aya ga mutane, kuma ka dubi ƙasusuwan ka gani yadda za Mu haɗa su, sannan Mu lulluɓe su da nama."To lokacin da komai ya bayyana a gare shi, sai ya ce: "Na sani lalle Allah Mai iko ne a kan komai."

260. Kuma ka tuna lokacin da Ibarahimu ya ce: “Ya Ubangijina, Ka nuna mini yadda Kake rayar da matattu.” Sai ya ce: “Shin ko ba ka yi imani ba ne?” Ya ce: “A’a, (na yi imani), sai dai ina son zuciyata ta ƙara samun nutsuwa.” Sai Ya ce: “To ka kama tsuntsaye huɗu ka tara su wajenka, sannan ka sanya yanka ɗaya-ɗaya nasu a kan kowane saman dutse, sannan ka kira su; za su zo maka da gaggawa. Kuma ka sani cewa lalle Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.”

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana a kan cewa imani haske ne kafirci kuma duffai ne, a waɗannan ayoyi sai ya kawo wasu hujjoji guda uku a kan hakan. Ta farko, kamar misali ne a kan hakan, domin labari ne da ya ƙunshi magana a kan ɓatan kafiri da shiriyar mumini. Allah yake gaya wa Annabinsa (ﷺ) labarin wani mutum da Allah ya ba shi mulki a zamanin Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), lokacin da giyar mulki ta kwashe shi, har ya yi da’awar allantaka. Ya tambayi Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), wane ne Ubangijinsa? Sai ya amsa masa da cewa: “Ubangijina shi ne wanda yake rayawa, yake kashewa.” Sai wannan sarki ya ce: “Ni ma ai ina rayawa, ina kuma kashewa.” Sai ya sa aka kawo masa wasu mutane su biyu, waɗanda aka yanke wa hukuncin kisa, ya sa aka zartar wa ɗayansu hukuncin kisa, ɗayan kuma ya sa aka sake shi. Sai ya ce, to ga shi ya raya wanda ya ga damar rayawa, kuma ya kashe wanda ya ga damar kashe shi. Sai Annabi Ibrahim ya fito masa ta wata hanyar daban, ya ce masa: “To ni Ubangijina a kullum yana fito da rana ta gabas, ta faɗi ta yamma, to kai sai ka fito da ita ta yamma idan za ka iya.” Jin haka ke da wuya, sai ya ruɗe, ya kiɗime, ya rasa hujjar riƙewa. To haka Allah yake yi wa azzalumai waɗanda suka zaɓi kafirci a kan imani, babu yadda za su sami wata hujja mai ƙarfi a kan kafircinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo misali na biyu, na wani bawan Allah da yake tsaka da tafiya, sai ya biyo ta wata alƙarya wadda mutanen cikinta gaba ɗaya sun mutu, ta zama kango babu komai cikinta sai kufai. Sai ya ka da baki ya ce: “Ta yaya Allah zai raya wannan alƙarya bayan mutuwarta?” Wato ta yaya wannan gari zai dawo ya ci gaba da rayuwa da mutanen cikinsa, kamar yadda yake a da? Nan take, sai Allah ya matar da shi, bai ɗawo masa da ransa ba, sai bayan shekara ɗari a mace. Bayan da ransa ya komo jikinsa, sai Allah ya tambaye shi: “Mene ne tsawon lokacin da ka zauna a wannan wuri?” Sai ya ce: “Ai na zauna yini ɗaya ne ko ma wani sashe na yini.” Wato ya zaci ɗan barci ne ya kwashe shi, kuma yanzu ya farka. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa masa da cewa: “Ai ka zauna a nan tsawon shekara ɗari ne, don haka ka dubi abincinka da abin shanka ba su sauya ba....” duk kuwa da shuɗewar waɗannan shekaru masu yawa, tare da kasancewarsu abin da ya fi komai saurin lalacewa, ya canza, “....amma kuma dubi jakinka, shi ya mutu har ƙasusuwansa sun ratattake.” To Allah ya yi masa haka ne don ya zama hujja ga mutane game da ikon Allah na tayar da matattu ranar lahira don yi musu hisabi. Allah ya ce wa wannan mutum, ya sake duba ratattakakkun ƙasusuwan jakinsa matacce, ya ga yadda Allah zai sake dawo masa da rayuwarsa, yadda zai lulluɓe waɗannan ƙasusuwa da nama, sannan ya sake hura masa rai, ya tashi ya koma kamar yadda yake a da, tamkar bai taɓa mutuwa ba. Yayin da wannan mutum ya gane wa idonsa abin da a da yake zaton wuyar faruwarsa, yanzu ga shi ya faru, sai ya tabbatar da cewa, Allah mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi, ko zai wahalar da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo dalili na uku, mai tabbatar da cewa, akwai ranar alƙiyama, kuma Allah zai tashi matattu daga ƙaburburansu, ya yi musu hisabi. Ya ba wa Annabi (ﷺ) labarin Annabi Ibrahim lokacin da ya nemi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna masa yadda yake raya matattu, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye shi: “Shin ko ba ka yi imani ba ne?” Annabin Allah Ibrahim ya amsa masa cewa, shi mumini ne, ba ya shakka ko kaɗan game da Kudurar Allah, sai dai manufar tambayarsa ita ce yana son ya ƙara imani ne, zuciyarsa ta ƙara nutsuwa. Sai Allah ya umarce shi da ya samo tsuntsaye huɗu, ya yanka su gunduwa-gunduwa, sannan ya je ya rarraba su a kan duwatsu daban-daban, sannan ya kirawo su, za su taho wajensa da gaggawa. Sai ya aikata, kamar yadda Allah ya umarce shi, sai ga tsuntsayen nan kowane ɗaya ya haɗe da jikinsa, sun zo wurinsa da sauri. Sai Allah ya

umarce shi da lalle ya sakankance cewa, Allah mabuwayi ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi sannan mai hikima ne, yana ajiye komai a muhallinsa da ya dace.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ladan Allah da falalarsa sun fi aikin mai aiki yawa. Da Allah ya mu'amalanci bawansa da adalcinsa ne, da sai ya ba shi lada guda a kan kowane aiki guda na alheri da ya yi, to amma sai ya mu'amalance shi da falalarsa, sai ya ninka masa ladan aikinsa ɗaya sau goma, har zuwa ɗari bakwai, kai har zuwa ninki ba iyaka.

2. A Musulunci ba kawai an shar'anta sadaka ba ne don toshe buƙatar mabuƙaci ko share masa hawaye ba; akwai manufar tsarkake zuciyar shi kansa mai bayarwar da motsa masa tausayinsa na ɗan'adam da alaƙarsa da mutum ɗan'uwansa, sannan da tuna masa ni'imar da Allah ya yi masa, ya kuma ƙulla alƙawari da shi a kan zai ciyar da ita saboda shi, ba tare da rowa ba, ko gori.

3. Wajibi ne a cikin duk ayyukanmu mu nufi abubuwa guda biyu: Na farko: neman yarda Allah. Na biyu; tsarkake zukatanmu daga duk wani abu marar kyau da zai jawo mana cikas, kamar rowa da zarmewa wajen son tara abin duniya ta kowace hanya, kuma aikata hakan mu zai yi wa amfani, Allah kuma Mawadaci ne ga kowa da komai.

4. Wanda duk ya yi riya wajen ciyar da dukiyarsa, to wannan alama ce ta tawayar imani tare da shi.

Suratul Baƙara (261-265)

مَّثَلُ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ كَمَثَلِ حَبَّةٍ أَنۢبَتَتۡ سَبۡعَ سَنَابِلَ فِي كُلِّ سُنۢبُلَةٖ مِّاْئَةُ حَبَّةٖۗ وَٱللَّهُ يُضَٰعِفُ لِمَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ٢٦١ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ ثُمَّ لَا يُتۡبِعُونَ مَآ أَنفَقُواْ مَنّٗا وَلَآ أَذٗى لَّهُمۡ أَجۡرُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡ وَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ٢٦٢ ۞ قَوۡلٞ مَّعۡرُوفٞ وَمَغۡفِرَةٌ خَيۡرٞ مِّن صَدَقَةٖ يَتۡبَعُهَآ أَذٗىۗ وَٱللَّهُ غَنِيٌّ حَلِيمٞ٢٦٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُبۡطِلُواْ صَدَقَٰتِكُم بِٱلۡمَنِّ وَٱلۡأَذَىٰ كَٱلَّذِي يُنفِقُ مَالَهُۥ رِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَلَا يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۖ فَمَثَلُهُۥ كَمَثَلِ صَفۡوَانٍ عَلَيۡهِ تُرَابٞ فَأَصَابَهُۥ وَابِلٞ فَتَرَكَهُۥ صَلۡدٗاۖ لَّا يَقۡدِرُونَ عَلَىٰ شَيۡءٖ مِّمَّا كَسَبُواْۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٢٦٤ وَمَثَلُ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمُ ٱبۡتِغَآءَ مَرۡضَاتِ ٱللَّهِ وَتَثۡبِيتٗا مِّنۡ أَنفُسِهِمۡ كَمَثَلِ جَنَّةِۭ بِرَبۡوَةٍ أَصَابَهَا وَابِلٞ فَـَٔاتَتۡ أُكُلَهَا ضِعۡفَيۡنِ فَإِن لَّمۡ يُصِبۡهَا وَابِلٞ فَطَلّٞۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٌ٢٦٥

261. Misalin waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu a hanyar Allah, kamar misalin ƙwaya ɗaya ce da ta fitar da zangarniya bakwai, a cikinta kowace zangarniya kuma (aka sami) ƙwaya ɗari. Kuma Allah Yana ninninkawa ga wanda Ya ga dama, kuma Allah Mai yalwa ne, Masani.

262. Waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu a hanyar Allah, sannan ba sa bin abin da suka ciyar da gori ko cuta, (waɗannan) suna da ladansu a wajen Ubangijinsu, kuma babu tsoro a tare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

263. Kyakkyawar magana da yafiya sun fi sadakar da cutarwa za ta biyo bayanta alheri. Kuma Allah Shi ne Wadatacce, Mai haƙuri.

264. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ɓata sadaƙoƙinku da gori da cutarwa, kamar wanda yake ciyar da dukiyarsa don mutane su gani, kuma ba ya imani da Allah da ranar lahira; to misalinsa kamar misalin kamfa ne da turɓaya take a kansa sai ruwan sama mamako ya same shi, sai ya bar shi tatas. Ba za su amfana da komai daga abin da suka aikata ba. Kuma Allah ba Ya shiryar da mutane kafirai.
265. Kuma misalin waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu don neman yardar Allah da tabbatar da (imani) a zukatansu, kamar misalin gona ce a kan jigawa sai ruwan sama mamako ya same ta, sai ta ba da amfaninta riɓi-biyu. To idan mamakon ruwan bai same ta ba, sai yayyafi (ya wadatar da ita). Kuma Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gama ambaton ƙissoshin da suke tabbatar da rayuwa bayan mutuwa, wato gaskiyar batun tashin alƙiyama, sai ya zo da ambaton abin da zai amfani mutum a wannan ranar, shi ne ciyar da dukiyarsa don Allah. Allah ya ba da misalin yadda yake ninka wa wanda ya yi sadaka da dukiyarsa sakamakonsa ninkin baninkin. Ya kwatanta shi da manomin da zai yafa ƙwaya ɗaya ta iri a cikin ƙasar noma mai kyau, idan ta zo fitowa sai ta fitar da zangarniya bakwai, kowace zangarniya kuma tana ɗauke da ƙwaya ɗari, ka ga zangarniya bakwai ta koma ƙwaya ɗari bakwai ke nan. Kuma ba nan abin ya tsaya ba; Allah yana ƙara ninka wa wanda ya ga dama fiye da hakan, domin shi Allah mai yalwar falala ne, ya san wanda ya cancanta a ninka masa ladansa.
Uƙbatu ɗan Amr (Allah ya kara masa yarda) ya ce, wani mutum ya kawo wa Annabi (ﷺ) wata taguwa mai sanye da akalarta, ya ce, ya Manzon Allah (ﷺ), na ba da wannan taguwar don Allah. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ranar gobe ƙiyama kana da taguwa mai akala ɗari bakwai.” [Muslim #1892]. Annabi (ﷺ) kuma ya ce: “Duk wani aiki ɗaya na ɗan’adam ana ninka masa shi sau goma, har zuwa ninki ɗari bakwai. Allah ya ce: “Sai dai azumi, ni ne nake ba da sakayyarsa.” [Muslim #1151].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, duk waɗanda suke ba da dukiyarsu wajen ayyukan alheri, don neman yardar Allah, sannan ba su haɗa aikinsu da wani abun gori ko cutarwa ba, wato ba sa goranta wa wanda suka taimaka masa ko su riƙa nuna masa girman kai da wulaƙanci don sun taimake shi ko su riƙa wahalar da shi saboda alherin da suka taɓa yi masa a baya, to duk waɗanda suke da irin wannan siffa, suna da ladansu a wurin Ubangijinsu, kuma kada su ji wani tsoron abin da za su tarar in sun mutu, kuma kada su yi wani baƙin ciki game da abin da suka bari a nan duniya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin cewa, yi wa mai neman taimkao magana mai daɗi, idan ba zai sami biyan buƙatarsa ba ko yi masa kyakkyawar addu’a ko magana mai faranta masa rai, da rufa masa asiri da yafe masa idan ya yi wata magana marar daɗi lokacin gabatar da buƙatarsa, yin haka ya fi zama alheri, fiye da a ba shi sadakar da za a biyo ta da gori ko cutarwa gare shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) Mawadaci ne, ba ya da buƙatar duk wata sadaka da bayi za su yi, ballantana wadda za a haɗa ta da gori da cutarwa, kuma Allah Mai haƙuri ne, yana yafe wa wanda ya yi sadaka da gori ko cutarwa idan ya tuba ya nemi gafara.
An karɓo daga Abu Zarri (Allah ya kara masa yarda) ya ce, Annabi (ﷺ) ya ce: “Mutum uku Allah ba zai yi musu magana ba a ranar gobe ƙiyama: Mai gori, wanda ba zai yi kyauta ba sai ya haɗa da gori da mai sayar da hajarsa ta hanyar rantsuwar ƙarya da mai sakin tufarsa tana jan ƙasa.” [Muslim #106].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa muminai da kada su ɓata sadakarsu da gori da cutarwa ga wanda suka ba shi sadakar, sai aikinsu ya zama kamar aikin munafukin da yake yin sadaka da dukiyarsa ba don Allah ba, sai don mutane su gani su yabe shi, alhalin su ba su san cewa bai yi imani da Allah ba, bai yi imani da lahira ba, don haka kar ya sa rai a kan samun wani sakamako ranar lahira a wannan aikin nasa. Keƙashewar zuciyar munafuki da bushewarta wajen rashin amfanuwa da aikin alherinsa saboda rashin imani da Allah da ranar lahira, kamar wani kamfan dutse ne wanda ƙasa ta rufe shi, duk wanda ya hango shi daga nesa, zai yi zaton za a iya shuka a wurin har ta tofo ta yi yaɗo. Da zarar ruwan sama ya sauka a kansa, sai duk ya wanke wannan ƙasar, sai dutsen ya fito tatas, babu wata ƙasa a kansa wadda ake zaton za ta iya fitar da tsiro. To haka sadakar munafuki take, za ta tafi ne a banza, babu

wani lada a kanta, saboda ba a kafa ta a kan ginshiƙi na imani ba, ba a yi ta da wata kyakkyawar niyya ba. Idan alƙiyama ta tsaya, lokacin girbin ayyukan alheri ya yi, duk masu aiki suka riƙa karɓar ladan ayyukansu, to su waɗannan munafuƙan za su zo suna son su sami ladansu, amma sai su iske fayau ba komai, duk abin da suka aikata na sadaka ya bi iska, su neme shi sama da ƙasa su rasa, domin ba su yi shi don Allah ba. To sai aka yi kira ga muminai kada su zama kamar waɗannan munafuƙan, su ɓata ladan sadakokinsu ta hanyar gori da cutar da wanda suka ba wa sadakarsu. Kuma Allah ba ya datar da waɗanda suka kafirce masa, har su karɓi gaskiya, su yi sadakarsu don neman yardarsa, domin sun fi son zama cikin ɓarnarsu a kan shiriya, don haka sai ya kautar da zukatansu daga shiriya.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci waɗanda suke ciyar da dukiyarsu a kan ayyukan alheri da neman yardarsa, ba tare da nuna gori ko cutar da wani ba. Sun fitar da dukiyoyinsu bisa ganin damarsu, ba don wani ya tilasta su ba, ba kuma don ganin idon wani ba; sun yi haka ne saboda sun yi imani da cewa, ranar lahira Allah zai yi musu sakayya a kan ayyukansu na alheri. To sai Allah ya sifanta waɗannan da wata gona mai yawan itatuwa da shuke-shuke masu yawa a cikinta, tana kan wani wuri mai tudu, don haka sai amfanin cikinta ya yi matuƙar kyau; sai kuma ta kasance tana samun ruwan sama, ko mai yawa, don haka amfaninta ya daɗa ƙaruwa ya ninku, kai ko ma ɗan yayyafi ta samu, wannan ma ya wadatar da ita, za ta fitar da ‘ya’yan itatuwa masu yawa, saboda kyan wurin da take. To haka sadakar mumini take, Allah yana riɓanya masa ladansa, ko ya bayar da mai yawa ne ko kuma kaɗan, ba za ta taɓa tafiya a banza ba, domin ya yi ne don Allah don neman yardarsa, bisa tabbatar da imani a zuciyarsa. Kuma Allah yana ganin duk abin da bayinsa suke yi, zai kuma yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayar da misali da abin da ake gani a zahiri don a fahinci abin da ba a ganin sa a zahiri.

2. Aiki da hankali don fahintar abin da ya dace.

3. Ana sadaka ne da dukiya ta halal, ba ta haram ba.

4. Idan mutum zai yi sadaka, to ya bayar da abin da yake mai daraja, ba abin da ya lalace ba.

5. Duk wani ilimi da hankali da mutum ya samu, to ya sani wata falala ce Allah ya yi masa, don haka ya wajaba a kansa ya yi amfani da wannan falala cikin abin da zai jawo masa yardar Allah.

6. Babu waɗanda wa’azi yake amfana sai masu cikakken hankali.

7. Bayar da sadaka a ɓoye ya fi a bayyana ta a fili, domin an fi samun ikhlasi a cikinta. Amma idan akwai wata maslaha wajen bayyana ta a fili, kamar mutum ya yi sadaka a gaban mutane don su ma su gani su kwaikwaye shi ko don cire wani zargi daga zuciyar wasu, to babu laifi mutum ya yi hakan.

8. Allah ya yi umarnin ba wa mabuƙata sadaka, amma bai taƙaita bayar da ita ga Musulmi kaɗai ba, wannan ya nuna ana iya ba da sadaka har ga kafiri, idan ya nemi taimako.

9. Shiriya ba a hannun kowa take ba tana ga hannun Allah ne. Don haka aikin mai karantarwa da wa’azi shi ne faɗar gaskiya; ba za a kama shi da laifin mutane idan sun ƙi karɓar wannan gaskiyar ba; za a kama shi ne kawai da laifin ya ƙi faɗa musu gaskiya.

10. Wanda duk ya hana wani ya ba da dukiyarsa saboda Allah, to wannan ya yi kama da Shaiɗan a aikinsa.

Suratul Bakara (266-274)

أَيَوَدُّ أَحَدُكُمْ أَن تَكُونَ لَهُۥ جَنَّةٌ مِّن نَّخِيلٍ وَأَعْنَابٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ لَهُۥ فِيهَا مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ وَأَصَابَهُ ٱلْكِبَرُ وَلَهُۥ ذُرِّيَّةٌ
ضُعَفَآءُ فَأَصَابَهَآ إِعْصَارٌ فِيهِ نَارٌ فَٱحْتَرَقَتْ ۗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلْءَايَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَتَفَكَّرُونَ ﴿٢٦٦﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ أَنفِقُوا۟ مِن
طَيِّبَٰتِ مَا كَسَبْتُمْ وَمِمَّآ أَخْرَجْنَا لَكُم مِّنَ ٱلْأَرْضِ ۖ وَلَا تَيَمَّمُوا۟ ٱلْخَبِيثَ مِنْهُ تُنفِقُونَ وَلَسْتُم بِـَٔاخِذِيهِ إِلَّآ أَن تُغْمِضُوا۟ فِيهِ ۚ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ
ٱللَّهَ غَنِىٌّ حَمِيدٌ ﴿٢٦٧﴾ ٱلشَّيْطَٰنُ يَعِدُكُمُ ٱلْفَقْرَ وَيَأْمُرُكُم بِٱلْفَحْشَآءِ ۖ وَٱللَّهُ يَعِدُكُم مَّغْفِرَةً مِّنْهُ وَفَضْلًا ۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٦٨﴾ يُؤْتِى ٱلْحِكْمَةَ
مَن يَشَآءُ ۚ وَمَن يُؤْتَ ٱلْحِكْمَةَ فَقَدْ أُوتِىَ خَيْرًا كَثِيرًا ۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُو۟لُوا۟ ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿٢٦٩﴾ وَمَآ أَنفَقْتُم مِّن نَّفَقَةٍ أَوْ نَذَرْتُم مِّن نَّذْرٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ
يَعْلَمُهُۥ ۗ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ﴿٢٧٠﴾ إِن تُبْدُوا۟ ٱلصَّدَقَٰتِ فَنِعِمَّا هِىَ ۖ وَإِن تُخْفُوهَا وَتُؤْتُوهَا ٱلْفُقَرَآءَ فَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ ۚ وَيُكَفِّرُ عَنكُم مِّن
سَيِّـَٔاتِكُمْ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿٢٧١﴾ * لَّيْسَ عَلَيْكَ هُدَىٰهُمْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَهْدِى مَن يَشَآءُ ۗ وَمَا تُنفِقُوا۟ مِنْ خَيْرٍ فَلِأَنفُسِكُمْ ۚ وَمَا
تُنفِقُونَ إِلَّا ٱبْتِغَآءَ وَجْهِ ٱللَّهِ ۚ وَمَا تُنفِقُوا۟ مِنْ خَيْرٍ يُوَفَّ إِلَيْكُمْ وَأَنتُمْ لَا تُظْلَمُونَ ﴿٢٧٢﴾ لِلْفُقَرَآءِ ٱلَّذِينَ أُحْصِرُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ لَا يَسْتَطِيعُونَ
ضَرْبًا فِى ٱلْأَرْضِ يَحْسَبُهُمُ ٱلْجَاهِلُ أَغْنِيَآءَ مِنَ ٱلتَّعَفُّفِ تَعْرِفُهُم بِسِيمَٰهُمْ لَا يَسْـَٔلُونَ ٱلنَّاسَ إِلْحَافًا ۗ وَمَا تُنفِقُوا۟ مِنْ خَيْرٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ بِهِۦ
عَلِيمٌ ﴿٢٧٣﴾ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَٰلَهُم بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ سِرًّا وَعَلَانِيَةً فَلَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٢٧٤﴾

266. Shin yanzu ɗayanku zai so a ce yana da wata gona ta itacen dabino da kuma inabai, wadda ƙoramu suke gudana a ƙarƙashinta, yana da dukkan wasu nau'uka na 'ya'yan itace a cikinta, sai kuma girma ya kama shi, kuma ga shi yana da yara raunana, sai kuma wata irin guguwa mai ɗauke da wuta ta same ta, sai (gonar gaba ɗaya) ta ƙone? Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyi don ku riƙa yin tunani.

267. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ciyar daga daɗaɗan abin da kuka tsuwurwuta da kuma abin da muka fitar muku shi daga cikin ƙasa, kuma kar ku nufaci mummuna daga cikinsa ku ce daga gare shi ne za ku ciyar, alhalin ku ma kanku (idan an ba ku) ba za ku karɓe shi ba sai kun runtse idanu. Kuma ku sani cewa lalle Allah Mawadaci ne, Sha-yabo.

268. Shaiɗan ne yake tsoratar da ku da talauci, kuma yana umartar ku da alfasha; Allah kuwa Yana yi muku alƙawarin gafara ta musamman daga gare Shi da kuma falala. Kuma Allah Mai yalwa ne, Masani.

269. Yana bayar da hikima ga wanda Ya ga dama; kuma dukkan wanda aka bai wa hikima, to haƙiƙa an ba shi alheri mai tarin yawa. Kuma ba wanda yake wa'azantuwa sai ma'abota hankula.

270. Kuma abin da kuka ciyar na abin ciyarwa ko kuka yi alwashi na bakance, to lalle Allah Yana sane da shi. Kuma azzalumai ba su da waɗansu mataimaka.

271. In da za ku bayyanar da sadakoki a fili, to madalla da hakan, kuma idan kuka ɓoye sadaƙar, kuma kuka ba da ita ga talakawa, to hakan shi ya fi alheri a gare ku, kuma zai kankare muku kurakurenku, kuma Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne.

272. Shiryar da su ba a kanka yake ba, sai dai Allah ne Yake shiryar da wanda Ya ga dama, kuma duk abin da kuka ciyar na alheri, to domin kawunanku ne, kuma ba za ku ciyar ba sai don neman yardar Allah; kuma duk abin da kuka ciyar na alheri, za a cika muku ladansa, alhali kuma ba za a zalunce ku ba.

273. Ga mabuƙata waɗanda aka tsare saboda Allah, ba su da ikon yawatawa a bayan ƙasa, har wanda ya jahilci halinsu yana zato su mawadata ne saboda kame kai; za ka gane su ne da alamominsu, ba sa naciyar roƙar mutane, kuma duk abin da kuka ciyar na alheri, to Allah Yana sane da shi.
274. Waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu dare da rana a ɓoye da kuma a sarari, to suna da ladansu a wajen Ubangijinsu, kuma babu tsoro a tare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin wanda yake gori a sadakarsa ko yake yin riya a cikinta, inda ya yi kira ga duk masu aikata irin wannan mummunan aiki da cewa, shin ɗaya daga cikinsu yana fatan a ce ya mallaki gona mai cike maƙil da itatuwan dabino da inabi, ga ƙoramu suna ta gudu a cikinta, sannan ta ƙunshi duk wani nau'i na 'ya'yan itatuwa da shuke-shuke, bayan haka kuma mai gonar shekarunsa sun yi nisa, amma kuma ƙaunarsa da wannan gonar a kullum sai ƙaruwa take saboda ita ce gatansa; ba ya iya fita wani aikin ƙarfi ko kasuwanci, ga shi kuma da 'ya'ya ƙanana, waɗanda shi ne mai ciyar da su. Yana cikin tsananin buƙata ga wannan gonar, sai Allah ya aiko da wata jarraba ta wata ƙaƙƙarfar iska mai ɗauke da wuta, wannan gonar duk ta ƙone ƙurmus?
To idan mai wannan gonar ya zo ya ga yadda ta zama, wane irin baƙin ciki ne ba zai yi ba? Yaya zuciyarsa a lokacin za ta kasance? Ga shi dai ya tsiyace, ga tsufa ga tarin iyali da ƙarfinsu bai kawo ba, balle su amfane shi. To kamar haka ne misalin wanda ya ba da dukiyarsa sadaka da farko don Allah, sannan daga baya ya ɓata sadakar da gori da kuma cutarwa; sai ya zo lokacin da yake da tsananin buƙatar wannan ladan, wato bayan mutuwarsa, sai ya samu wannan aiki nasa duk ya lalace, babu wani abin da zai mora a cikinsa. Da irin waɗannan bayanai ne Allah yake fito da ayoyinsa sarari don bayinsa su yi tunani su faɗaka.
Wata rana Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce wa sahabban Annabi (ﷺ): A zatonku wannan aya da Allah yake cewa: "Shin yanzu ɗayanku zai so a ce yana da wata gona...." a kan me ta sauka? Sai suka ce: "Allah ne mafi sani." Sai Umar ya yi fushi, ya ce: "Kawai ku ce mun sani, ko kuma ba mu sani ba." Sai Ibn Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Ya Sarkin Muminai, ni akwai wani abu da nake tunani game da wannan ayar." Sai Umar ya ce: "Ɗan ɗan'uwana, faɗi abin da yake ranka, kada ka raina kanka." Sai Ibn Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Misalin wani aiki ne aka bayar." Sai Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Wane irin aiki?" Sai Ibn Abbas ya ce: "Wani aiki dai." Sai Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Misalin wani mai kuɗi ne wanda yake aikin ɗa'a ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sai Allah ya sallaɗa masa da Shaiɗan, ya koma ayyukan saɓon Allah, har sai da suka lalata ayyukan ɗa'arsa." [Bukhari #4538].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar da bayinsa da su fitar da zakkar dukiyoyinsu kuma su yi sadaka daga mafi kyan dukiyar da suka mallaka ta halal da amfanin gonar da suka noma ko ma'adinan da suka haƙo; kada kuma su kuskura su fitar da zakkarsu ko su bayar da sadaka daga cikin gurɓatacciyar dukiyarsu wadda ta lalace, wadda idan su aka ba wa ita a matsayin sadaka ko kyauta, duk buƙatarsu ba za su so irinta ba, sai dai su karɓa hakanan, ba don suna so ba. Allah ya umarce su da su san da cewa shi Allah Mawadaci ne, ba ya da buƙatar komai a wurinsu, yana kwaɗaitar da su ne da su yi sadaka domin su ne za su amfana da ladan idan sun yi. Sannan kuma shi Allah Sha-yabo ne, saboda duk siffofinsa na kamala ne, kuma duk abin da yake umarni da shi mas'laha ce da rahama ga mutane.
Albara'u ɗan Azib yana cewa game da faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): "Kuma kada ku nufaci mummuna daga cikinsa, ku ce daga gare shi za ku ciyar....," ya ce: "A kanmu ne mu mutanen Madina masu gonakin dabino wannan ayar ta sauka, kowannenmu yana fito da dabinon gonarsa gwargwadon yawansa da ƙanƙantarsa, nono ɗaya ko biyu ya rataye shi a cikin masallacin Annabi (ﷺ), su kuma ahlus-suffah, wato talakawan da suke kwana a masallacin, waɗanda ba su da wani abincin da suke samu su ci, don haka idan ɗayansu ya ji yunwa, sai ya sa sanda ya daki wannan nonon dabinon na rataye, sai dabinon ya zubo ƙasa, sai ya ɗauka ya ci.
To akwai wasu mutane da ba sa ƙaunar aikata alheri, sai ɗayansu ya ɗauko nonon dabino wanda ya lalace, ya zo ya rataye shi a masallaci. Sai Allah ya saukar da wannan ayar, yana cewa: "Ya ku waɗanda

suka yi imani, ku ciyar daga daɗaɗan abin da kuka tsuwurwurta, da kuma abin da muka fitar muku daga ƙasa, kuma kar ku nufaci mummuna daga cikinsa, ku ce daga gare shi za ku ciyar, alhalin ku ma kanku (idan an ba ku) ba za ku karɓe shi ba, sai kun runtse idanu." Al-Bara'u ya ce: "Da za a yi wa ɗayanku kyauta da abin da shi ya bayar kyauta, to da ba zai karɓa ba, sai ya runtse ido, ko ya karɓa cikin jin nauyi." Al-Bara'u ya ce: "Daga wannan ranar kowa sai ya riƙa kawo dabino mai kyau." [Tirmizi #2987].
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa bayinsa muminai cewa, Shaiɗan ne yake tsoratar da su da cewa za su talauce idan suna sadaka da dukiyoyinsu, yana umartar su da rowa da aikata kowane irin saɓon Allah da miyagun ayyuka. Shi kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa bayinsa alƙawarin gafara ne game da laifin da za su yi, su tuba daga baya, kuma yana yi musu alƙawarin zai mayar musu da duk abin da suka bayar sadaka na dukiyarsu, kuma zai haɓaka musu arzikinsu, ya ƙara yawan ladansu, domin shi Allah mai yalwar falala ne, kuma mai cikakken sani. Yana ba da hikima ga wanda ya ga dama daga bayinsa, ya ba su damar fahintar manufofin hukunce-hukuncensa da sirrin da yake cikin yi masa ɗa'a da saɓa wa tafarkin Shaiɗan. Duk kuma wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa hikima cikin bayinsa, to lalle ya ba shi alheri mai yawa, amma ba kowa ne yake ganewa ya wa'azantu ba, sai masu cikakken hankali.
Annabi (ﷺ) yana cewa: "Hassada ba ta halatta sai ga mutum biyu. Mutumin da Allah ya ba shi dukiya, sannan ya ba shi ikon kashe ta inda ya dace. Sai kuma mutumin da Allah ya ba shi hikima (ilimi), ya kasance yana hukunci da ita, yana kuma karantar da ita." [Bukhari #73, Muslim #816]. Watau mutum ya ji a ransa shi ma yana son samun irin haka.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da bayinsa cewa, duk wata sadaka da za su bayar ko wani bakance da za su wajabta wa kansu, to Allah yana sane da shi, babu abin da yake ɓoye masa, kuma zai yi sakayya a kai. Duk kuma wanda zai zo ranar alƙiyama, bai fitar da zakkarsa ba ko bai sauke bakancensa ba, to babu wanda zai iya taimaka masa a ranar, ya kuɓutar da shi daga kamun Ubangiji (Mai tsarki da ɗaukaka).
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa bayinsa cewa, idan suka fitar da sadakarsu ta neman lada suka bayar da ita a fili, to madalla da abin da suka yi, matuƙar dai ba da nufin riya ba. Idan kuma sun fitar sun bayar da ita a ɓoye, to yin hakan shi ya fi falala a wurin Allah. Kuma Allah zai kankare musu laifukansu da irin wannan sadakar ta ɓoye, ko ta sarari, Allah yana ganin duk ayyukansu, kuma zai yi musu sakayya a kai.
Malaman tafsiri sun haɗu a kan cewa, wannan ayar tana magana ne a kan sadakar da aka yi ta nafila, ba zakka ba. Ita zakka an fi son bayyana ta a fili, domin ita alama ce ta tabbatar Musuluncin mutum, kuma da wannan ne zai tsare dukiyarsa. Amma sadakar neman lada an fi son a ɓoye ta, sai dai idan akwai wata maslaha da aka hango game da bayyana ta, to sai a bayyana ta babu komai.
Annabi (ﷺ) ya ambaci wasu mutane su bakwai da Allah zai saka su a inuwar Al'arshinsa, ranar da babu wata inuwa sai inuwarsa; daga cikinsu akwai mutumin da ya yi sadaka da hannunsa na dama, ya ɓoye ta har hannunsa na hagu ma bai san abin da hannun damansa ya bayar ba." [Bukhari #1423, da Muslim #1031].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, shiriyar mutane ba a hannunsa take ba; abin da yake wajibi a kansa shi ne ya isar musu da saƙon da Allah ya aiko shi da shi, shi kuma Allah shi ne yake kimsa shiriya a zuciyar wanda ya ga dama daga cikin bayinsa.
Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: "Musulmi sun ji damuwa game da ba wa 'yan'uwansu na jini kafirai sadakar dukiyarsu, saboda kafircinsu, sai suka tambayi Annabi (ﷺ) game da haka, sai Allah ya saukar da wannan ayar." [Musnadul Bazzar #5042, At-Tabrani #12453, Alhakim 2:313].
Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) kuma yana cewa: "Da farko an umarce mu da kada mu bayar da sadaka sai ga Musulmi, har sai da wannan ayar ta sauka, sai Annabi (ﷺ) ya umarce mu da mu bayar da sadaka ga duk wanda ya nema, daga kowane addini yake." [Ibni Abi Hatim, Tafsir 2:537].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, sadakar da masu dukiya suke yi, su za ta amfana, kuma sadakar da za ta amfani mai yin ta ita ce wadda mutum ya yi don Allah shi kaɗai, tare da fatan ya

sami ganin fuskar Allah ranar alƙiyama. Kuma duk abin da bayinsa suka bayar sadaka a nan duniya, za su sami cikakken ladansa ranar lahira, babu abin da zai salwanta a ciki.
A nan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin waɗanda suka fi cancantar a taimaka musu da sadaka, watau waɗanda aka tsare su ko suka ba da kansu domin jihadi saboda ɗaukaka kalmar Allah, da bayar da kariya ga Musulmi da Musulunci, don haka ba sa fita ko'ina don neman arziki ko don kasuwanci, ta yadda wanda bai san su ba idan ya gan su, ya ga kawaicinsu da kamewarsu da rashin nuna kwaɗayinsu ga abin duniya, sai ya zaci su masu kuɗi ne. Abin da kawai zai sa a gane su shi ne alamun buƙata da talauci, wanda sai mai nutsuwa da kaifin hankali zai gani a fuskarsu ko ya gane ta wasu maganganunsu, amma su kwata-kwata ba sa roƙon mutane, ballantana har su nace wajen roƙon su. Sannan Allah ya bayyana cewa, sadakar da muminai suka bayar kaɗan ne ko mai yawa, to Allah yana sane da ita, kuma zai yi musu sakamako a kai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawari ga waɗanda suke ciyar da dukiyarsu dare da rana, a sarari da ɓoye cewa, suna da sakamako babba a wurin Ubangijinsu ranar lahira, babu wani abin tsoro da zai same su a nan gaba, kuma ba za su yi baƙin ciki ba game da abin da ya wuce, don haka dai za su sami abin da suke so, kuma za su tsira daga abin da suke ƙi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dole ne Musulmi ya ƙudurce da cewa, babu wani al'amari wanda rayuwar ɗan'adam ba za ta yiwu ba sai da shi, kuma ya zamana Allah ya haramta shi, kamar yadda dole ne ya ƙudurce cewa, babu wani abu wanda zai cutar da rayuwar ɗan'adam, sannan wannan abin ya zamanto rayuwar ɗan'adam ta tsayu a kansa, ko ta samu ci gaba a sanadiyyarsa.

2. Hukunci na ƙarshe na Allah ne shi kaɗai, shi ne mai haƙƙin ya halatta abu ko ya haramta shi, duk hukuncin da ya yanke, to dole ne mumini ya sallama; ya gane hikimar da ke cikinsa ko bai gane ba.

3. Abin da mutum ya ci na riba, kafin ya san hukuncin haramcinsa, to halal ne a gare shi, da sharaɗin ya tuba, ya hanu daga wannan laifin.

4. Idan mai karɓar riba ya san hukuncinta kafin ya karɓa, to bai halatta a gare shi ya karɓi abin da ya sharaɗanta ba kafin ya sani kuma ya tuba.

5. Idan mai cin riba yana yaƙi ne da Allah da Manzonsa, to yana yaƙi ne da duk wani mumini, saboda wajibi ne a kan kowane mimini ya shiga yaƙin da ake yi da Allah da Manzonsa da taimakawa, domin muminai duka rundunar Allah ce da Manzonsa.

6. Dole ne Musulmi ya yi watsi da kowace irin riba a ƙarƙashin kowane irin suna aka kirawo ta.

7. Tabbatar da adalci a cikin mu'amaloli na mutane, ba cuta ba cutarwa.

8. Falalar yafe bashi ga wanda yake cikin matsatsi ko rage masa yawan bashin.

9. Tabbatar da bugun aljanu ga mutane har su kamu da hauka.

Suratul Baƙara (275-281)
ٱلَّذِينَ يَأۡكُلُونَ ٱلرِّبَوٰاْ لَا يَقُومُونَ إِلَّا كَمَا يَقُومُ ٱلَّذِي يَتَخَبَّطُهُ ٱلشَّيۡطَٰنُ مِنَ ٱلۡمَسِّۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَالُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡبَيۡعُ مِثۡلُ ٱلرِّبَوٰاْۗ وَأَحَلَّ ٱللَّهُ ٱلۡبَيۡعَ وَحَرَّمَ ٱلرِّبَوٰاْۚ فَمَن جَآءَهُۥ مَوۡعِظَةٞ مِّن رَّبِّهِۦ فَٱنتَهَىٰ فَلَهُۥ مَا سَلَفَ وَأَمۡرُهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِۖ وَمَنۡ عَادَ فَأُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا

خَٰلِدُونَ ﴿٢٧٥﴾ يَمۡحَقُ ٱللَّهُ ٱلرِّبَوٰاْ وَيُرۡبِي ٱلصَّدَقَٰتِۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ كَفَّارٍ أَثِيمٍ ﴿٢٧٦﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ لَهُمۡ أَجۡرُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡ وَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ﴿٢٧٧﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَذَرُواْ مَا بَقِيَ مِنَ ٱلرِّبَوٰٓاْ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ﴿٢٧٨﴾ فَإِن لَّمۡ تَفۡعَلُواْ فَأۡذَنُواْ بِحَرۡبٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۖ وَإِن تُبۡتُمۡ فَلَكُمۡ رُءُوسُ أَمۡوَٰلِكُمۡ لَا تَظۡلِمُونَ وَلَا تُظۡلَمُونَ ﴿٢٧٩﴾ وَإِن كَانَ ذُو عُسۡرَةٖ فَنَظِرَةٌ إِلَىٰ مَيۡسَرَةٖۚ وَأَن تَصَدَّقُواْ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ﴿٢٨٠﴾ وَٱتَّقُواْ يَوۡمٗا تُرۡجَعُونَ فِيهِ إِلَى ٱللَّهِۖ ثُمَّ تُوَفَّىٰ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا كَسَبَتۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ﴿٢٨١﴾

275. Waɗanda suke cin riba ba za su tashi ba (daga ƙaburburansu) sai kamar tashin mutumin da Shaiɗan yake bige shi da hauka. Hakan zai faru ne don sun ce: “Lalle kasuwanci kamar riba yake.” Kuma Allah Ya halatta kasuwanci, kuma Ya haramta riba. To duk wanda wa’azi ya zo masa daga wurin Ubangijinsa, sai ya daina, to abin da ya wuce a baya ya zama nasa, kuma al’amarinsa yana wurin Allah; wanda kuma ya sake komawa daga baya, to waɗannan su ne ma’abota wuta, suna masu dawwama a cikinta.

276. Allah Yana shafe albarkar riba, Yana kuma haɓaka sadaƙa. Kuma Allah ba Ya son dukkan wani mai yawan kafircewa, mai yawan saɓo.

277. Lalle waɗanda suka yi imani kuma suka yi ayyuka nagari kuma suka tsayar da salla, kuma suka bayar da zakka, to suna da ladansu a wajen Ubangijinsu, kuma babu jin tsoro a gare su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

278. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku rabu da abin da ya yi ragowa na riba in har kun kasance muminai.

279. Idan kuwa ba ku aikata haka ba, to ku saurari wani yaƙi daga Allah da Manzonsa; idan kuwa kun tuba, to uwar kuɗin taku ce, ba za ku yi zalunci ba, ku ma kuma ba za a zalunce ku ba.

280. Kuma idan (mai cin bashin) ya kasance ma’abocin matsi, to sai a yi masa jinkiri zuwa lokacin da zai sami sauƙi, kuma in da za ku yi sadaƙa shi ya fi alheri a gare ku in kun kasance kuna da masaniya.

281. Kuma ku kiyayi wani yini da za a mayar da ku zuwa ga Allah a cikinsa, sannan kowane rai za a cika masa abin da ya aiwatar na aiki, kuma su ba za a zalunce su ba.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gama bayanin mutanen kirki, masu ba da dukiyarsu don Allah, suna taimaka wa mabuƙata da talakawa, sai kuma ya kawo bayani cikin waɗannan ayoyi a kan masu cin dukiyar riba da dukiyar da aka tara ta haramtacciyar hanya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, maciya riba ranar alƙiyama ba za su tashi daga ƙaburburansu lafiya lau ba, a’a, za su tashi ne kamar waɗanda Shaiɗan ya shafe su da ciwon hauka, saboda a nan duniya sun riƙa da’awar cewa, ai da saye da sayarwa da Allah ya halatta, da kuɗin riba, duk abu ɗaya ne, wai duk hanya ce ta neman kuɗi, me zai sa a halatta ɗaya, a kuma haramta ɗayar? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaryata wannan da’awar tasu, ya ce, duk wata riba da mutum zai samu ta hanyar kasuwanci to ta halatta, amma an haramta masa cin kuɗin riba, watau ba da bashi da ruwa, domin ba ɗaya suke ba. Duk wanda hukuncin hana cin kuɗin riba ya zo masa, ya daina, to shi ke nan babu komai a kansa game da abin da ya riga ya wuce, kuma al’amarinsa yana wurin Allah, ko dai ya yi masa gyaɗar dogo ya ci gaba da tsayuwa a kan cin

halal, ko kuma ya taɓar da shi, ya koma ruwa. To amma fa duk wanda ya kuskura ya koma ga cin riba bayan ya san da haramcinta, amma ya dage a kai, to wannan shi ya cancanta shiga wuta, ya dawwama a cikinta, babu abin da zai hana shi dawwama a wuta sai imaninsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, yana shafe albarkar dukiyar riba, yana kuma haɓaka ladan wanda ya ba da dukiyarsa sadaka, har dukiyarsa ita ma za ta haɓaka a dalilin hakan. Allah ba ya son wanda yake yawan butulce wa ni'imominsa, yake kuma halatta cin kuɗin riba, ya zarce cikin saɓon Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi alƙawari ga waɗanda suka yi imani, kuma suka yi ayyuka nagari, kuma suka tsayar da salla kamar yadda ya kamata, sannan kuma suka ba da zakkar dukiyarsu ga waɗanda ya dace su ba da cewa, ladansu yana nan wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma ba tsoro a tattare da su game da abin da za su tarar bayan mutuwarsu, hakanan babu wani baƙin ciki da za su yi game da abin da suka bari a nan duniya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da yi wa muminai wa'azi da gargaɗi, da su ji tsoron Allah, su yi watsi da duk wata mu'amala ta riba wadda suke cikin ƙulla ta yayin da wannan gargaɗi ya zo musu, idan dai da gaske suke su muminai ne. Idan kuma sun ƙi ji, sun ƙi bari, to su sanar da kawunansu, su kuma sanar da wasu masu irin aikinsu cewa, Allah da Manzansa suna shelanta yaƙi da su. Idan kuma sun tuba, sun daina mu'amalar riba, to su karɓi uwar kuɗinsu da suka bayar bashi, kada su karɓi komai a kai, idan kuwa sun yi haka to sun yi zalunci, kamar yadda su ma kada wani ya zalunce su, ya ƙi biyan su kuɗaɗensu gaba ɗaya. Amma idan shi wanda ake bin sa bashi ba shi da abin biya, yana cikin hali na matsi, to su ɗan saurara masa har Allah ya hore masa, ko kuma su rage masa shi, wannan ya fi musu alheri in da a ce sun san irin gwaggwaɓar ladan da za su samu.
Sahabin nan na Annabi (ﷺ), Abu Katada (Allah ya kara masa yarda), an ce yana bin wani bashi, sai ya riƙa buya, har wata rana ya same shi, sai ya ce masa: "Ina cikin halin matsi ne, ba ni da abin biya." Sai Abu Katada ya ce: "Za ka rantse da Allah?" Ya ce: "Na rantse da Allah." Sai Abu Katada ya ce: "Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Duk wanda zai yi farin ciki Allah ya tseratar da shi daga baƙin cikin ranar lahira, to ya sassauta wa wanda yake bi bashi yana cikin matsuwa ko ma ya yafe masa duka." [Muslim #1563].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi gargaɗi da a kiyayi wani yini wanda idan ya zo, duk wani abu da mutum yake tinƙaho da shi a nan duniya, na dukiya ko waninta, zai gushe, kuma za a mayar da kowa zuwa ga mahalaccinsa Allah; a ranar lahira zai saka wa kowa a kan irin ayyukan da ya zo da su, don haka babu abin da zai amfani mutum a ran nan sai aikinsa na ƙwarai, kuma kowa za a ba shi sakamakonsa cikakke, ba tare da an tauye masa komai ba na ladansa, ko a ƙara masa wani laifi a kan laifukansa.
Abdullahi ɗan Abbas yana cewa: "Wannan ayar ita ce ta ƙarshen sauka a Alƙur'ani." [Dubi: An-Nasa'i: *At-Tafsir* #77, 78; Ibn Jarir #6311].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yadda Musulunci ya ba wa sha'anin ibada muhimmanci, haka ya ba wa lamarin mu'amalar mutane a tsakaninsu muhimmanci. Ayar da ta fi kowacce tsawo a Alƙur'ani, ita ce wannan ayar da take magana a kan sha'anin mu'amala ta bashi.

2. Muhimmancin ilimi da koyon karatu da rubutu.

3. Bayanin girman sha'anin bashi.

4. Fifikon jinsin namiji a kan jinsin mace wajen ƙarfin lura da kiyaye al'amura.

5. Ba a karɓar shaidar wanda ba Musulmi ba ko wanda yake ba adali ba.

Suratul Baƙara (282-283)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا تَدَايَنتُم بِدَيۡنٍ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى فَٱكۡتُبُوهُۚ وَلۡيَكۡتُب بَّيۡنَكُمۡ كَاتِبُۢ بِٱلۡعَدۡلِۚ وَلَا يَأۡبَ كَاتِبٌ أَن يَكۡتُبَ كَمَا عَلَّمَهُ ٱللَّهُۚ فَلۡيَكۡتُبۡ وَلۡيُمۡلِلِ ٱلَّذِي عَلَيۡهِ ٱلۡحَقُّ وَلۡيَتَّقِ ٱللَّهَ رَبَّهُۥ وَلَا يَبۡخَسۡ مِنۡهُ شَيۡـٔٗاۚ فَإِن كَانَ ٱلَّذِي عَلَيۡهِ ٱلۡحَقُّ سَفِيهًا أَوۡ ضَعِيفًا أَوۡ لَا يَسۡتَطِيعُ أَن يُمِلَّ هُوَ فَلۡيُمۡلِلۡ وَلِيُّهُۥ بِٱلۡعَدۡلِۚ وَٱسۡتَشۡهِدُواْ شَهِيدَيۡنِ مِن رِّجَالِكُمۡۖ فَإِن لَّمۡ يَكُونَا رَجُلَيۡنِ فَرَجُلٞ وَٱمۡرَأَتَانِ مِمَّن تَرۡضَوۡنَ مِنَ ٱلشُّهَدَآءِ أَن تَضِلَّ إِحۡدَىٰهُمَا فَتُذَكِّرَ إِحۡدَىٰهُمَا ٱلۡأُخۡرَىٰۚ وَلَا يَأۡبَ ٱلشُّهَدَآءُ إِذَا مَا دُعُواْۚ وَلَا تَسۡـَٔمُوٓاْ أَن تَكۡتُبُوهُ صَغِيرًا أَوۡ كَبِيرًا إِلَىٰٓ أَجَلِهِۦۚ ذَٰلِكُمۡ أَقۡسَطُ عِندَ ٱللَّهِ وَأَقۡوَمُ لِلشَّهَٰدَةِ وَأَدۡنَىٰٓ أَلَّا تَرۡتَابُوٓاْ إِلَّآ أَن تَكُونَ تِجَٰرَةً حَاضِرَةٗ تُدِيرُونَهَا بَيۡنَكُمۡ فَلَيۡسَ عَلَيۡكُمۡ جُنَاحٌ أَلَّا تَكۡتُبُوهَاۗ وَأَشۡهِدُوٓاْ إِذَا تَبَايَعۡتُمۡۚ وَلَا يُضَآرَّ كَاتِبٞ وَلَا شَهِيدٞۚ وَإِن تَفۡعَلُواْ فَإِنَّهُۥ فُسُوقُۢ بِكُمۡۗ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۖ وَيُعَلِّمُكُمُ ٱللَّهُۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ٢٨٢ * وَإِن كُنتُمۡ عَلَىٰ سَفَرٖ وَلَمۡ تَجِدُواْ كَاتِبٗا فَرِهَٰنٞ مَّقۡبُوضَةٞۖ فَإِنۡ أَمِنَ بَعۡضُكُم بَعۡضٗا فَلۡيُؤَدِّ ٱلَّذِي ٱؤۡتُمِنَ أَمَٰنَتَهُۥ وَلۡيَتَّقِ ٱللَّهَ رَبَّهُۥۗ وَلَا تَكۡتُمُواْ ٱلشَّهَٰدَةَۚ وَمَن يَكۡتُمۡهَا فَإِنَّهُۥٓ ءَاثِمٞ قَلۡبُهُۥۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ عَلِيمٞ ٢٨٣

282. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka ba wa junanku bashi zuwa wani lokaci sananne, to ku rubuta shi, kuma a sami wani marubuci da zai rubuta a tsakaninku da adalci, kuma marubucin kar ya ƙi rubutawa kamar yadda Allah ya sanar da shi. Don haka ya rubuta, kuma shi wanda haƙƙi yake kansa sai ya yi shifta gare shi, kuma ya ji tsoron Allah Ubangijinsa, kuma kada ya tauye wani abu a cikinsa. To idan wanda haƙƙi yake kansa ya kasance wawa ne ko mai rauni ko ba shi da ikon ya yi shifta shi da kansa, to sai majiɓincin lamarinsa ya yi shifta (a madadinsa) da adalci, kuma ku kafa shaidu biyu cikin mazajenku; kuma idan ba su kasance mazaje biyu ba, to sai a nemi namiji ɗaya da mata biyu daga shaidun da kuka yarda da su, saboda idan ɗaya daga cikinsu ta manta sai ɗayar ta tuna mata, kuma kada shaidun su ƙi zuwa idan an kiraye su, kuma kada ku ƙosa, ku rubuta shi, kaɗan ne ko da yawa, zuwa cikar wa'adinsa. Abin da aka ambata mukun nan shi ne ya fi zama adalci a wajen Allah, kuma ya fi daidaita shaida, kuma shi ya fi kusata ku ta yadda ba za ku yi shakka ba, sai dai idan ya kasance ciniki ne hannu da hannu da kuke gudanar da shi tsakaninku; to babu laifi a kanku idan ba ku rubuta shi ba. Kuma ku kafa shaida idan kun yi hulɗa ta ciniki, kuma kada marubuci ya yi cuta, haka shi ma mai shaida (kada ya yi cuta). Idan kuwa har kuka aikata haka, to lalle wannan fasiƙanci ne a gare ku. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma Allah Yana sanar da ku (dokokinsa). Kuma Allah Masanin komai ne.

283. Kuma idan kun kasance a halin tafiya, kuma ba ku sami marubuci ba, to sai a ba da jingina da za a karɓa, kuma idan sashinku ya amince wa sashi, to shi wanda aka amincewan ya bayar da amanarsa, kuma ya kiyayi Allah Ubangijinsa. Kuma kada ku ɓoye shaida; duk wanda ya ɓoye ta kuwa, to lalle shi zuciyarsa a cike take da saɓo. Kuma Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin yadda ya kamata muminai su gudanar da harkar bashi a tsakaninsu, inda ya umarce su da cewa, idan sun yi wata mu'amala ta bashi a tsakaninsu zuwa wani lokaci sananne, to su rubuta abin da suka yi yarjejeniya a kansa a tsakaninsu, don gudun mantawa ko jayyaya a nana gaba. Wanda duk zai rubuta wannan yarjejeniyar tasu, ya zamana ya iya rubutu kuma adali ne, mai gaskiya. Wanda duk ya iya rubutu kuma aka neme shi da rubuta irin wannan yarjejeniya, to kada ya ce ba zai yi ba. Ya tuna cewa, Allah ne ya ba shi wannan ilimin na rubutu, kuma shi ne ya umarce shi da ya rubuta musu. Kuma wanda zai riƙa faɗa ana rubutawa, shi ne wanda ya ci bashin da kansa, kuma ya ji tsaron Allah, kada ya rage wa mai haƙƙi komai cikin haƙƙinsa. To idan wanda bashin yake kansa ya zamanto wawa ne ko yaro ne, wanda ba zai iya komai ba ko kuma mai taɓin hankali ne ko kuma dai ba zai iya shifta ba saboda wani dalili da zai hana shi yi, to sai waliyyinsa wanda yake kula da al'amuransa ya yi shiftar, kuma shi ma lalle ya yi gaskiya, ya yi adalci a yayin shiftar.

Hakanan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiryar da bayinsa muminai a kan su kafa shaidu biyu maza Musulmai adalai, idan ba a samu maza ba, to sai a kafa shaida da namiji ɗaya da mata biyu su ma adalai amintattu, domin idan ɗaya ta manta, sai ɗayar ta tunatar da ita. Kuma su ma shaidun su sani bai dace a gare su ba, idan an kirawo su su zama shaidu, ko su bayar da shaidar da suka sani, su ce ba za su zo ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nusar da bayinsa cewa, kada su ƙosa wajen rubuta mu'amalar kowane irin bashi ne, kaɗan ne ko mai yawa, zuwa ga wa'adinsa, domin rubuta bashi da tantance lokacinsa, ya fi adalci a wurin Allah, kuma zai fi taimaka wa masu ba da shaida, ta yadda ba za a sami saɓani a tsakaninsu ba, domin dukkansu za su dogara da abin da aka rubuta ne, kamar yadda yin hakan zai kawar da duk wani kokwanto. Amma idan ciniki ne tsakanin mai saye da mai sayarwa kowa zai karɓi haƙƙinsa a nan take, to babu laifi don ba a rubuta komai a lokacin ba, amma dai yana da kyau duk da haka a sami shaidu.
Haka kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana masu haƙƙi su cutar da mai rubutawa ko mai shaida; mai rubutun da mai shaidar su ma kada su cutar da masu haƙƙi ta kowace hanya, domin yin haka saba wa Allah ne. Sannan Allah ya umarce su da su zama masu taƙawa, ya kuma sanar da su cewa, yana koyar da su hukunce-hukuncen shari'arsa ne domin rahama gare su; shi kuma masanin komai ne, babu abin da yake ɓuya a gare shi, don haka zai yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shar'anta wa muminai cewa, yayin da suke cikin halin tafiya, kuma suka ƙulla mu'amalar bashi zuwa wani sanannen lokaci, kuma ba su sami wanda zai rubuta masu ba a daidai lokacin, to sai su bi wata hanyar daban don tabbatar da wannan bashi, watau wanda ya bayar da bashin ya karɓi wani kayan jingina daga wurin wanda ya ci bashin, ya ajiye a wurinsa, har sai ya biya bashin, sai ya mayar masa da abinsa. Idan kuwa shi mai bayar da bashin ya amince wa wanda zai karɓi bashin, ya ba shi ba tare da wata jingina ba, to shi wanda ya ci bashin ya yi ƙoƙari ya dawo masa da haƙƙinsa cikkake, ya guji saba wa Allah, don kada ya kama shi da laifin saba wa umarninsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana ɓoye shaida, ko dai ta hanyar rinto, ko kuma ta hanyar ƙari ko ragi a kan abin da yake gaskiya, Allah ya sifanta wanda yake ɓoye shaida a matsayin wanda zuciyarsa take cike da saɓon Allah, kuma Allah yana sane da duk ayyukan bayinsa, zai yi musu sakamako gwargwadon aikin kowa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi da jan kunne ga mumuni da kada ya kuskura ya ce zai ɓoye wani abu a zuciyarsa wanda Allah bai yarda da shi ba, domin duk abin da ka ɓoye a zuciyarka Allah yana sane da shi, kuma zai yi hisaba a kansa.

2. Bayanin halin muminai da yadda suke bayyana gajiyawarsu da rauninsu gaba ga Ubangijinsu, don haka suke neman mafaka a wurinsa suke neman taimakonsa da afuwarsa.

3. Bayani a kan cewa, Allah bai ɗora wa bayinsa wani abu a addini wanda ya fi ƙarfinsu ba. Addini gaba ɗayansa mai sauƙi ne, don haka ɗan'adam ba shi da wata hujjar barin koyarwa ta addini ya kama wata.

Suratul Baƙara (284-286)

لِّلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَإِن تُبۡدُواْ مَا فِيٓ أَنفُسِكُمۡ أَوۡ تُخۡفُوهُ يُحَاسِبۡكُم بِهِ ٱللَّهُۖ فَيَغۡفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ
كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ٢٨٤ ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّن
رُّسُلِهِۦۚ وَقَالُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۖ غُفۡرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيۡكَ ٱلۡمَصِيرُ ٢٨٥ لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفۡسًا إِلَّا وُسۡعَهَاۚ لَهَا مَا كَسَبَتۡ وَعَلَيۡهَا مَا ٱكۡتَسَبَتۡۗ رَبَّنَا

لَا تُؤَاخِذۡنَآ إِن نَّسِينَآ أَوۡ أَخۡطَأۡنَاۚ رَبَّنَا وَلَا تَحۡمِلۡ عَلَيۡنَآ إِصۡرٗا كَمَا حَمَلۡتَهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِنَاۚ رَبَّنَا وَلَا تُحَمِّلۡنَا مَا لَا طَاقَةَ لَنَا بِهِۦۖ وَٱعۡفُ عَنَّا وَٱغۡفِرۡ لَنَا وَٱرۡحَمۡنَآۚ أَنتَ مَوۡلَىٰنَا فَٱنصُرۡنَا عَلَى ٱلۡقَوۡمِ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٢٨٦

284. Duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa na Allah ne. Kuma in har kuka bayyana abin da yake cikin zukatanku ko kuka ɓoye shi, Allah zai yi muku hisabi a kansa, sai Ya yi gafara ga wanda Ya ga dama, Ya kuma yi azaba ga wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai.

285. Manzon ya yi imani da abin da aka saukar masa daga Ubangijinsa, muminai ma haka, kowanne ya yi imani da Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa, (suna cewa) : "Ba ma nuna bambanci tsakanin ɗaya daga cikin manzanninsa." Kuma suka ce: "Mun ji kuma mun bi ; muna neman gafararka ya Ubangijinmu, kuma zuwa gare Ka ne makoma take.

286. Allah ba Ya kallafa wa rai sai abin da zai iya. Abin da ya aikata (na alheri) nasa ne, hakanan sakamakon abin da ya aikata (na sharri) shi ma nasa ne. Ya Ubangijinmu, kada Ka riƙe mu da laifi idan mun yi mantuwa ko mun yi kuskure. Ya Ubangijinmu, kada kuma Ka ɗora mana wani nauyi irin wanda ka ɗora wa waɗanda suke gabaninmu. Ya Ubangijinmu, kada kuma Ka ɗora mana abin da ba mu da iko a kansa, kuma Ka yi mana afuwa, kuma Ka yi mana gafara, kuma Ka ji ƙan mu; Kai ne Majiɓincin lamarinmu, don haka Ka taimake mu a kan mutane kafirai.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gama bayanin abubuwan da wannan Sura ta ƙunsa, waɗanda suka ƙunshi dalilan kaɗaitar Ubangiji, da ingancin annabci da gaskiyar tashin alƙiyama da bayanin salla da zakka da ƙisasi da azumi da Hajji da jihadi da haila da saki da idda da khul'i da ila'i da shayarwa da riba da kasuwanci da hukuncin bashi, sai kuma a nan Allah yake bayinin cewa, shi ne mamallakin sammai da ƙasa, yana da damar ya lizimta wa bayinsa duk hukuncin da ya ga dama, saboda su bayinsa ne, kuma yana sane da duk abin da yake zukatansu, don haka zai yi musu hisabi a kan abin da suka bayyana da wanda suka ɓoye a zukatansu, daga nan sai ya gafarta wa wanda ya ga dama, ya azabtar da wanda ya ga dama, babu abin da zai gagare shi, domin shi mai iko ne a kan komai.
Abu Hurairah (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Lokacin da wannan ayar ta sauka, abin ya yi wa sahabbai tsanani, sai suka je wurin Annabi (ﷺ), suka gurfana a gabansa, suka ce: "Ya Manzon Allah, an kallafa mana ayyukan da za mu iya aikatawa, kamar salla da azumi da jihadi da sadaka, kuma ga shi an saukar maka da wannan ayar, wadda ba za mu iya ɗaukar ta ba." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce musu: "Kuna so ne ku faɗi irin abin da Yahudawa da Nasara suka faɗi a gabaninku cewa, sun ji kuma sun ƙi? A'a, ku sai ku ce: "Mun ji, mun bi, kuma ka yi mana gafara, ya Ubangijinmu, kuma zuwa gare ka makoma take." To lokacin da sahabbai suka ci gaba da faɗar haka, har harshensu ya saba da haka, sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Manzo ya yi imani da abin da aka saukar masa daga Ubangijinsa, muminai ma haka, kowanne ya yi imani da Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa…." har zuwa ƙarshen ayar. Yayin da suka yi haka, sai Allah ya shafe wancan hukuncin da ya saukar da faɗarsa: "Allah ba ya kallafa wa rai sai abin da zai iya, abin da ya aikata na alheri nasa ne, hakanan sakamakon abin da ya aikata na sharri shi ma nasa ne. Ya Ubangijinmu, kada ka riƙe mu da laifi idan mun yi mantuwa, ko mun yi kuskure." Allah ya ce: 'Na'am!' "Ya Ubangijinmu, kada kuma ka ɗora mana wani nauyi irin wanda ka ɗora wa waɗanda suke gabaninmu." Allah ya ce: 'Na'am!' Ya Ubangijinmu, kada kuma ka ɗora mana abin da ba mu da iko a kansa. Allah ya ce: 'Na'am!' "Kuma ka yi mana afuwa, kuma ka yi mana gafara, kuma ka ji ƙan mu; kai ne majiɓincin lamarinmu, don haka ka taimake mu a kan mutanen da suke kafirai." Allah ya ce: 'Na'am!' [Muslim #125].
Annabi (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya karanta ayoyi biyu na ƙarshen Suratul Baƙara da daddare, sun ishe shi." [Bukhari #5008].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas ya ce, wata rana mala'ika Jibrilu yana zaune tare da Manzon Allah (ﷺ), sai ya ji wata ƙara a samansa, sai ya ɗaga kansa ya ce: "Wannan wata ƙofa ce a sama da aka buɗe ta a yau, ba a taɓa buɗe ta ba sai yau, sai wani mala'ika ya sauko ta wannan ƙofar, ya ce: "Wannan wani mala'ika ne da ya sauka ƙasa, bai taɓa saukowa ba sai yau, sai ya yi sallama ya ce: "Albishirinka, ga wani haske guda biyu da aka ba ka, ba a taɓa ba da su ga wani annabi ba gabaninka, su ne Fatihatul Kitabi, da ayoyin ƙarshen Suratul Baƙara, duk wani harafi da za ka karanta daga cikinsu sai an ba ka abin da ka roƙa." [Muslim #806].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kasancewar dalilin saukar ayoyin farko na wannan Sura shi ne jayayyar da Nasaran Najrana suka yi da Annabi (ﷺ) dangane da sha'anin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai ya zamana ya dace a buɗe wannan Sura da waɗannan haruffa, waɗanda suke ishara zuwa ga ƙalubalantar masu ƙaryata Alƙur'ani.

2. Faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cewa: "Allah, babu abin bauta wa da gaskiya sai shi...." mayar da martani ne ga Nasara masu cewa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ne.

3. Siffofin nan na Allah guda biyu, (Rayayye da Tsayayye da Zatinsa) haɗa su wuri guda yana nuna siffantuwar Allah da dukkan siffofi na kamala. 'Rayayye' yana nufin kamalar siffofinsa duka, 'Tsayayye da Zatinsa' yana nufin kamalar ayyukansa gaba ɗaya, don haka sun ƙunshi kamalar Zati, da kamalar ayyuka.

4. Attaura da Linjila shiriya ne ga mutane a lokacinsu, amma bayan saukar da Alƙur'ani, babu wata shiriya da ta rage sai ta Alƙur'ani kaɗai.

5. Musulunci shi ne addinin gaskiya, wanda ya haɗa bautar Allah shi kaɗai da kuma imani da annabawan Allah gaba ɗaya.

3 Ali-Imran

Mabuɗin Surar

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna *Suratu Ali Imran* saboda a cikinta aka ambaci falalar iyalan gidan Imrana.
An Karɓo daga An-Nawwas ɗan Sam'anu (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "A ranar alƙiyama za a zo da Alƙur'ani tare da makarantansa waɗanda suke aiki da shi, Suratul Baƙara da Ali Imaran suna yi musu jagoranci". [Muslim #805].
An karɓo daga Abu Umamata Al-Bahili (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Ku karanta masu haske biyu: *Suratul Baƙara da Ali-Imaran*." [Muslim #804].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa an saukar da Suratu Ali Imaran ne a Madina, wato bayan hijira.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce ta arba'in da takwas (48) a jerin saukar surorin Alƙur'ani.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin yawancin malamai adadin ayoyinta ɗari biyu ne (200), amma a lissafin mutanen Sham adadinsu ɗari da tis'in da tara ne (199).

5. Sababin Saukarta:
Tun farkon Surar har zuwa aya ta 83 sun sauka ne game da sha'anin ƙungiyar Nasara da suka zo Madina wurin Annabi (ﷺ) a shekara ta tara bayan hijira, don haka ne yawancin ayoyinta sun yi magana a kan Annabi Isa Almasihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). [Dubi, Al-Kurɗubi, Juzu'i na 4, Shafi na 4 da Ibnu Kasir, Juzu'i na 2, Shafi na 5].

6. Falalarta:
Za ta jagoranci masu karatunta a ranar alƙiyama, kamar yadda ya gabata a hadisin An-Nawwas (ﷺ.). Za su ba da kariya ga makarantansu:
An Karɓo daga Abu Umamata Al-Bahili (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku karanta Alƙur'ani zai zo ranar alƙiyama yana mai ceto ga makarantansa. Ku karanta masu haske biyu: *Suratul Baƙara* da *Suratu Ali Imaran*, domin za su zo ranar alƙiyama kamar gizagizai biyu, ko kuma kamar garke biyu na tsuntsaye waɗanda suka jeru sahu-sahu suna bayar da kariya ga makarantansu." [Muslim #804].
Sahabbai suna girmama wanda ya haddace *Suratul Baƙara* da *Ali Imran*:
An karɓo daga Anas (ﷺ.) ya ce: "Idan wani mutum a cikin mu ya karance Baƙara da Ali Imaran sai darajarsa ta ɗaukaka." [Ahmad #12236, da Ibn Hibban #744].

7**. Babban Jigonta:**
• Tabbatar da Kaɗaitar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da kafa hujjoji da dalilai a kan haka.

• Gargaɗin muminai game da jiɓintar waɗanda ba muminai ba, da bayanin halayen ma'abota Littafi, watau Yahudawa da Nasara.
• Ba da muhimmanci a kan sha'anin tarbiya da nusarwa ga muminai.

8. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin Kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da tabbatar da rabe-raben Tauhidi guda uku: *Uluhiyya da Rububiyya* da kuma Sunaye da Siffofin Allah.
• Tabbatar da cewa duka saukakkun littattafai daga Allah suke gaba ɗaya.
• Rarrabuwar mutane wajen imani da ayoyin Alƙur'ani masu bayyanannun hukunce-hukunce, da masu rikitarwa.
• Gargaɗin kafirai maƙiya Allah da Manzonsa da nuna musu cewa iko da ƙarfi da dukiya da 'ya'ya ba za su amfana musu komai ba ko su kare musu azabar Allah a duniya da lahira, kamar yadda ba su amfani kafiran da suka gabace su ba, irin su Fir'auna.
• Ishara zuwa ga yaƙin Badar da bayanin abubuwan da suka faru a yaƙin Uhudu.
• Bayanin abin da ɗan'adam yake sha'awa a ransa tare da nuna masa abin da ya fi masa alheri, watau abin da Allah ya tanadar masa a lahira na ni'ima madawwamiya.
• Bayanin halayen ma'abota Littafi daki-daki da tona asirinsu da bayanin saɓanin da ke tsakaninsu na addini da aika-aikarsu ta ƙaryata ayoyin Allah da kashe annabawa da masu wa'azi da rashin miƙa wuya ga hukuncin da ya zo musu a littafin Allah da kiran da Manzon Allah ya yi wa wanda yake jayayya daga cikinsu zuwa ga *mubahala watau* addu'ar tsinuwa). Sai kuma umarnin da aka ba wa Manzon Allah na ya kirawo su zuwa ga kalmar Tauhidi da jayayya da su game da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da faɗa musu gaskiya a kansa.
• Faɗakarwa a kan ƙaunar juna tsakanin muminai da kuma nisantar kafirai da guje wa jiɓintar maƙiya Allah da Manzonsa ko ɗaukar su abokan shawara.
• Bayanin cewa, son Allah ba a baka yake ba kwai; dole ne sai an bi Mazon Allah tukunna an yi masa ɗa'a cikin umarninsa da haninsa.
• Ambaton annabawa da bayinin matsayinsu da zaɓin Allah gare su, da kuma bayanin ƙissar Annabi Isa da mahaifiyarsa da ƙissar Annabi Zakariyya da ɗansa Annabi Yahya.
• Ambaton wasu daga cikin halaye na ƙwarai da tarbiyyantar a'ummar Musulmi a kansu, kamar wasiyya da tsoron Allah da taƙawa da riƙe igiyar Allah da watsi da rarrabuwar kai da rungumar kira zuwa ga Allah da sauran halaye na ƙwarai da Surar ta yi tsokaci a kansu.
• Ambaton wasu daga cikin hukunce-hukuncen shari'a, kamar hana cin riba da satar dukiyar ganima da uƙubar masu hana zakka

Suratu Ali-Imran (1-4)

الٓمٓ ۝١ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡحَيُّ ٱلۡقَيُّومُ ۝٢ نَزَّلَ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِ وَأَنزَلَ ٱلتَّوۡرَىٰةَ وَٱلۡإِنجِيلَ ۝٣ مِن قَبۡلُ هُدٗى لِّلنَّاسِ وَأَنزَلَ ٱلۡفُرۡقَانَۗ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ لَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٞۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٞ ذُو ٱنتِقَامٍ ۝٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. *Alif Laam Miim*.

2. Allah, babu wani abin bautawa da gaskiya sai Shi, Shi Rayayye ne, Tsayayye da Zatinsa.

3. Ya saukar maka da Littafi da gaskiya, yana mai gaskata abin da ya gabace shi, kuma Ya saukar da Attaura da Linjila.

4. Tun kafin (Alƙur'ani), (don su zama) shiriya ga mutane, kuma Ya saukar da mai rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya). Lalle waɗanda suka kafirce wa ayoyin Allah, suna da azaba mai tsanani, kuma Allah Mabuwayi ne, Ma'abocin ɗaukar fansa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da haruffa kamar yadda ya yi a *Suratul Baƙara*, domin bayanin mu'ujizar Alƙur'ani, don nuna babu mai iya kawo kamarsa, duk kuwa da cewa magana ce da ta ƙunshi haruffa na Larabawa irin waɗanda suke rubutu da su. Sannan Allah ya yi bayanin Allantakarsa da cewa, shi ne abin bauta na gaskiya, wanda daga cikin siffofinsa, shi ne Rayayye, mai cikakkiyar rayuwa, wadda ta siffantu da dukkan siffofi na kamala, Tsayayye da Zatinsa, ba shi da buƙata a wurin wani cikin halittarsa, kuma shi ne mai tsayawa da taimakon kowa da komai, don haka kowa yana da buƙata a wurinsa. Daga cikin taimakonsa da rahamarsa ga bayinsa, shi ne ya aiko musu da Annabi (ﷺ), ya kuma saukar masa da Alƙur'ani, wanda yake cike da gaskiya, kuma yake gaskata littattafan da suka gabace shi. Kuma Allah ya saukar da Attaura ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Linjila ga Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) tun kafin saukar da Alƙur'ani. Allah ya saukar da littattafan nan ne dukkansu saboda shiriyar da mutane. A cikinsu Allah ya saukar da abin da yake bambancewa tsakanin ƙarya da gaskiya da tsakanin shiriya da ɓata, saboda haka Allah ya yi alƙawarin azaba mai tsanani ga waɗanda suka kafirce wa ayoyinsa a ranar gobe ƙiyama. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) babu wanda zai iya rinjayar sa, kuma babu abin da zai gagare shi, kuma shi mai gaggawar ɗaukar fansa ne ga wanda ya saɓa masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jan hankalin ɗan'adam a kan ya kyautata halayensa, ya kyautata ayyukansa, domin Allah Mahaliccinsa yana ganin sa, babu abin da yake ɓuya a gare shi.

2. Yana daga cikin alamomin karkacewar zuciya, bibiyar ayoyin Alƙur'ani masu rikitarwa, don mutum ya saka kansa ko wasu cikin shakka.

3. Idan mai karatu ya yi waƙafi a daidai ﴿إِلَّا ٱللَّهُ﴾ to hakan yana nuna a cikin Alƙur'ani akwai abin da babu wanda ya san fassararsa sai Allah. Fassara a nan, ko kuma *'tawili',* kamar yadda ya zo a ayar, ana nufin ƙarshen al'amari, ko kuma yadda haƙiƙanin al'amarin zai kasance. A nan akwai jarrabawa da Allah yake yi wa bayinsa game da abubuwan da ba za su iya fahintar su da tsurar hankalinsu ba. Shin za su ce sai sun gano su ta haka, ko kuwa za su sallama wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), su tsaya a matsayinsu?

4. Babu masu jayayya da abin da ya zo daga Allah sai masu ƙaramin sani, waɗanda ba su yi zurfi ba a cikin ilimi. Wannan yana nuna falalar yin ilimin shari'a mai zurfi, domin yana taimakawa wajen samun tsayuwa a kan gaskiya.

5. Daga wannan aya za mu fahimci cewa akwai abin da ake kira 'ilimi', akwai kuma kafuwa da zurfi cikin ilimin, don haka mai neman ilimi kada ya haƙura da ɗan kaɗan, ya yi ƙoƙarin kafuwa da zurfi a cikinsa.

6. Babu mai amfana da wa'azuzzukan Alƙur'ani sai masu hankali. Duk sa'adda hankalin mutum ya ƙaru; to fahintarsa ga Alƙur'ani za ta ƙaru, duk sa'adda ka ga ba ya wa'azantuwa da Alƙur'ani; to hakan yana nuna ƙarancin hankalinsa ne.

7. Zuciya tana da hali guda biyu, halin daidaita da kuma halin karkata, don haka mutum a ko da yaushe yana buƙatar ya riƙa roƙon Allah da kada zuciyarsa ta karkace, domin ba a hannunsa take ba, tana

hannun Allah ne, shi ne yake yin yadda ya ga dama da ita, don haka kada mutum ya ruɗu da kansa, ya dogara a kan imaninsa, sau tari an sami mai imanin da ya taɓe ya saki hanya.
8. Idan mutum ya samu kuɓuta daga fitinar shubuha, da fitinar sha'awa; to ya gama samun manyan buƙatunsa biyu na duniya da lahira, su ne shiriya da rahama.

Suratu Ali-Imran (5-9)

إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَخۡفَىٰ عَلَيۡهِ شَيۡءٞ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِي ٱلسَّمَآءِ ۝٥ هُوَ ٱلَّذِي يُصَوِّرُكُمۡ فِي ٱلۡأَرۡحَامِ كَيۡفَ يَشَآءُۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ۝٦ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ مِنۡهُ ءَايَٰتٞ مُّحۡكَمَٰتٌ هُنَّ أُمُّ ٱلۡكِتَٰبِ وَأُخَرُ مُتَشَٰبِهَٰتٞۖ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِمۡ زَيۡغٞ فَيَتَّبِعُونَ مَا تَشَٰبَهَ مِنۡهُ ٱبۡتِغَآءَ ٱلۡفِتۡنَةِ وَٱبۡتِغَآءَ تَأۡوِيلِهِۦۖ وَمَا يَعۡلَمُ تَأۡوِيلَهُۥٓ إِلَّا ٱللَّهُۗ وَٱلرَّٰسِخُونَ فِي ٱلۡعِلۡمِ يَقُولُونَ ءَامَنَّا بِهِۦ كُلّٞ مِّنۡ عِندِ رَبِّنَاۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ۝٧ رَبَّنَا لَا تُزِغۡ قُلُوبَنَا بَعۡدَ إِذۡ هَدَيۡتَنَا وَهَبۡ لَنَا مِن لَّدُنكَ رَحۡمَةًۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡوَهَّابُ ۝٨ رَبَّنَآ إِنَّكَ جَامِعُ ٱلنَّاسِ لِيَوۡمٖ لَّا رَيۡبَ فِيهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُخۡلِفُ ٱلۡمِيعَادَ ۝٩

5. Lalle Allah babu abin da yake ɓoyuwa a gare Shi a ƙasa ko a sama.

6. Shi ne wanda Yake suranta ku a cikin mahaifu irin yadda Ya ga dama, babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi, Shi ne Mabuwayi, Mai hikima.

7. Shi ne Wanda ya saukar maka da Littafi, a cikinsa akwai ayoyi masu bayyanannun hukunce-hukunce, su ne asalin Littafin, akwai kuma waɗansu masu rikitarwa; to amma waɗanda suke da karkata a zukatansu sai su riƙa bin abin da yake rikitarwar a cikinsu don neman fitina da kuma neman sanin haƙiƙanin fassararsa. Kuma babu wanda ya san haƙiƙanin fassararsa sai Allah. Kuma masu zurfi cikin ilimi kuma suna cewa: "Mun yi imani da shi, dukkaninsa daga wurin Ubangijinmu yake." Kuma ba mai wa'azantuwa sai masu hankali.

8. "Ya Ubangijinmu, kada Ka karkatar da zukatanmu bayan Ka shiryar da mu, kuma Ka yi mana rahama daga gare Ka. Lalle kai Mai yawan baiwa ne."

9. "Ya Ubangijinmu, lalle Kai ne Mai tattara mutane a yinin da babu kokwanto a cikinsa. Lalle Allah ba Ya saɓa alƙawari."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin gamammen iliminsa, wanda ya kewaye komai, don babu wani abu da yake ɓuya a gare shi, a sama yake ko a ƙasa. Shi ne yake halittar ku bisa kamanni daban-daban a cikin cikin iyayenku yadda ya ga dama, don haka shi ne kaɗai ya cancanta a bauta wa; ba shi da wani abokin tarayya. Shi ne Mabuwayi a cikin mulkinsa; ba mai iya ja da shi ko ya fi ƙarfinsa, kuma shi mai hikima ne a cikin ayyukansa da shari'unsa, babu wani tasgaro a cikinsu ko kaɗan. Shi ne wanda ya saukar wa Annabi (ﷺ) Alƙur'ani, wanda ya ƙunshi ayoyin da suke a fili, ma'anoninsu a bayyane suke, babu wani abu mai rikitarwa tare da su, su ne kuma tushen wannan littafi, kuma su ne mafiya yawa a cikinsa. A cikinsa kuma akwai waɗansu ayoyi waɗanda ma'anarsu take da rikitarwa ga wasu mutane. To amma sai a samu waɗansu karkatattun mutane masu cutar kauce wa gaskiya a zukatansu, suna bibiyar waɗannan ayoyi masu rikitarwa, suna barin ayoyin da ma'anoninsu suke a fili, ba don komai ba sai don su ɓatar da mutane, su jefa shakka a zukatansu, don su sami wani abu da za su kafa hujja da shi a kan soye-soyen zukatansu. Su kuwa waɗannan ayoyi masu rikitarwa, babu wanda ya san haƙiƙanin fassararsu sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Malamai masu zurfin ilimi na Alƙur'ani su ma sukan san tafsirin ma'anonin ayoyin, amma ba za su iya sanin haƙiƙanin al'amarin ba, da yadda ƙarshen zai kasance, domin wannan Allah ne kaɗai ya san shi. Malamai masu zurfin ilimi sukan shelanta imaninsu

da waɗannan ayoyi masu rikitarwa. Duk kuma ayoyin na Alƙur'ani daga Allah ne, amma ba kowa ne yake wa'azantuwa ba sai masu lafiyayyen hankali.
An karɓo daga A'isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: "Annabi (ﷺ) ya karanta wannan ayar, sai ya ce: "Idan kika ga waɗanda suke bibiyar ayoyi masu rikitarwa a cikin Alƙur'ani; to su ne waɗanda Allah ya ambata, don haka ki guje su." [Bukhari #4547, Muslim #2665].
Malamai masu zurfin ilimi addu'a suke yi ko da yaushe, suna roƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kada ya karkatar da zukatansu su saki shiriya bayan Allah ya shiryar da su, ya yi musu rahama, ya ƙara musu imani da tsayuwa a kan gaskiya, domin Allah shi ne mai yawan kyauta da ihsani ga bayinsa. Kuma suna addu'a suna cewa: "Ya Allah kai ne za ka tara mutane a ranar Alƙiyama, ranar da babu shakka a zuwanta, domin yin hukunci da sakayya ga kowa a kan aikinsa, don haka ka gafarta mana a wannan ranar, ka yi mana afuwa." Sun kuma yi Imani da cewa, lalle Allah ba ya saɓa alƙawarinsa na cewa, wanda duk ya yi imani da shi, ya bi Manzonsa; to zai gafarta masa.
An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya kara masa yarda) ya ce, Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle zukatan 'yan'adam duka suna tsakanin yatsu biyu ne daga yatsun Allah Mai rahama, tamkar zuciya ɗaya, yana sarrafa su yadda ya ga dama." Sannan sai Annabi (ﷺ) ya yi addu'a yana cewa: "Ya Allah Mai sarrafa zukata, ka sarrafa zukatanmu a kan ɗa'arka." [Muslim #2654].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kada mutum ya ruɗu da yawan dukiya ko 'ya'ya ko wani ƙyale-ƙyale na duniya, su sa shi ya yi ta saɓa wa Allah; ranar da azabar Allah ta zo masa, duk waɗannan abubuwa ba za su amfane shi da komai a wurin Allah ba.

2. Mumini yana amfana da dukiyarsa da 'ya'yansa a lahira idan ya tafiyar da su kamar yadda Allah ya tsara masa.

3. Duk kafirci a wurin Allah iri ɗaya ne, na da da na yanzu, babu bambanci.4. Zunubban bayi su ne suke jawowa Allah ya halaka su, amma ba don zalunci ba. Allah ba azzalumin kowa ba ne.

5. Sunnar Allah yana gudanar da ita a kan kowa a kowane wuri, kuma a kowane zamani, don haka babu inda mai laifi zai gudu ya kuɓuta.

Suratu Ali-Imran (10-11)
إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗاۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ وَقُودُ ٱلنَّارِ ١٠ كَدَأۡبِ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ بِذُنُوبِهِمۡۗ وَٱللَّهُ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ١١

10. Lalle waɗanda suka kafirta, dukiyoyinsu da 'ya'yansu ba za su wadatar da su da komai ba a wajen Allah; kuma waɗannan su makamashi ne na wuta.

11. Kamar dai halin abin da ya gudana ga mutanen Fir'auna da waɗanda suka gabace su. Sun ƙaryata ayoyinmu, sai Allah Ya kama su da zunubansu, kuma Allah Mai tsananin uƙuba ne.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci ranar lahira, ya kuma tabbatar da cewa, rana ce da babu kokwanto ga zuwanta, ya kuma ambaci halin muminai na neman gafara da afuwar Allah a wannan ranar, sai kuma a waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo bayanin kafirai da yadda halinsu zai zamanto a wannan ranar. Allah Ta'ala ya bayyana cewa waɗanda suka kafirce wa Allah da ayoyinsa,

kuma suka ƙaryata manzanninsa, suka nuna musu ƙiyayya, kuma suka bijire wa addinin Allah; to waɗannan dukiyoyinsu da ‘ya’yansu ba za su taɓa yi musu amfani ba, kuma ba za su kuɓutar da su daga azabar Allah ba, yayin da ta zo musu. Makomarsu ita ce wutar Jahannama, su ne makamashinta da za a riƙa rura ta, kuma za su dawwama a cikinta har abada, babu ranar fitarsu. Wannan sunnar Allah ce wadda ba ta canzawa. Al’amarin waɗannan daidai yake da al’amarin Fir’auna da jama’arsa da sauran al’ummomin da suka ƙaryata Allah da manzanninsa, su ma haka Allah ya halakar da su saboda zaluncinsu, haka da ma Allah yake, mai tsananin uƙuba ne ga duk wanda ya bijire masa, ya ƙi tuba ya dawo gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Da a ce Musulmi za su koma ga addininsu na Musulunci, su yi riƙo da koyarwarsa ta aƙida da ibada da kyawawan halaye da kyakkyawar mu’amala; to da Allah ya ba su nasara da rinjaye a kan duk wani mai gaba da su, kamar yadda ya yi wa musulmin farko, har suka mallaki gabashin duniya da yammacinta.

2. Yaƙi shi kaɗai ba zai sa a sami nasara ba, har sai idan ya kasance don Allah aka yi shi, kuma an kiyaye dokokin Allah a cikinsa.

3. Yawan sojoji ko mayaƙa ba shi ne yake sa a sami cin nasarar yaƙi ba; ana samun nasara ne da taimakon Allah da ɗaukinsa.

4. Wajibi ne mu ɗauki darusa daga rayuwar al’ummomin da suka gabace mu, mu aikata abin da suka yi Allah ya taimake su ya ba su nasara, mu nesanci aikin da wasunsu suka yi Allah ya halakar da su duniya da lahira.

5. Duk mutumin da ba ya wa’azantuwa; to wannan alama ce da take nuna raunin basirarsa da hangen nesansa.

Suratu Ali-Imran (12-13)
قُل لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ سَتُغۡلَبُونَ وَتُحۡشَرُونَ إِلَىٰ جَهَنَّمَۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ١٢ قَدۡ كَانَ لَكُمۡ ءَايَةٞ فِي فِئَتَيۡنِ ٱلۡتَقَتَاۖ فِئَةٞ تُقَٰتِلُ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَأُخۡرَىٰ كَافِرَةٞ يَرَوۡنَهُم مِّثۡلَيۡهِمۡ رَأۡيَ ٱلۡعَيۡنِۚ وَٱللَّهُ يُؤَيِّدُ بِنَصۡرِهِۦ مَن يَشَآءُۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّأُوْلِي ٱلۡأَبۡصَٰرِ ١٣

12. Ka ce wa waɗanda suka kafirta: "Da sannu za a rinjaye ku, kuma za a tara ku zuwa Jahannama. Kuma tir da wannan mashimfiɗi.

13. Haƙiƙa wata izina ta bayyana a gare ku game da wasu rundunoni biyu da suka gwabza, ɗaya rundunar tana yaƙi saboda Allah, ɗayar kuma kafira ce, suna kallon su (musulmi) kamar ninki biyu a ganin ido; kuma Allah Yana ƙarfafar wanda Ya ga dama da nasararsa. Lalle a cikin hakan akwai izina ga ma'abota basira.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Manzonsa (ﷺ) da ya faɗa wa kafirai cewa, muminai sai sun yi rinjaye a kansu a rayuwarsu ta duniya, sannan idan ranar alƙiyama ta tsaya, a tarkata su gaba ɗaya cikin wutar Jahannama, domin ita ce shimfiɗar da suka tanadar wa kawunansu tun a nan duniya. Tir kuwa da wannan shimfiɗa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana wa kafirai ko kuma muminai cewa, sun ga alama a fili da ta nuna muminai ne za su yi rinjaye a kan kafirai, kuma Allah ya yi alƙawarin zai ɗaukaka addininsa, kuma

ya ƙarfafi Manzonsa. Wannan alama ita ce, ƙungiyoyin mayaƙa biyu da suka haɗu don kafsa yaƙi a tsakaninsu. Kungiyar farko muminai ne, masu yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah, su ne Annabi da Musulmi a yaƙin Badar; ɗaya ƙungiyar kuma kafirai ne, suna yaƙi ba don Allah ba, su ne Kuraishawa kafiran Makka a ranar Badar. A lokacin muminai suna ganin kafirai a ido, sun ninka su gida biyu. Wannan kuwa ya ƙara musu dogaro ga Allah da neman taimakonsa, wanda yin hakan yana daga cikin dalilan samun nasara. Haka Allah yake ƙarfafar wanda ya ga dama da samun nasara. To yadda Allah ya ba wa waɗannan muminai 'yan kaɗan nasara a kan abokan gabarsu masu yawa, akwai darasi da wa'azi ga duk wanda Allah ya ba shi basira da hangen nesa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rage nuna damuwa ga ƙyale-ƙyalin duniya, mai gushewa nan da nan da himmatuwa wajen neman lahira, mai dawwama har abada.

2. Duk yawan abin duniyar da bawa zai samu; to jin daɗi ne na wucin-gadi, zai mutu ya bar shi. Ni'ima ta har abada ita ce ni'imar lahira.

3. Waɗannan ni'imomi da aka ambata a nan, ya kamata bawa ya kalle su ta fuskar da za su amfane shi, ba kallo irin na sha'awa ba. Idan ya yi haka to za su fi ƙarfin zuciyarsa, har su karkatar da shi daga kan hanyar gaskiya.

4. Gargaɗi ga mai saɓa wa Allah cewa, Allah yana ganin duk aikin da yake yi, kuma zai saka masa a kai.
5. Kowace ɗaya daga cikin sifofin masu tsoron Allah da Allah ya ambata, sifa ce mai matuƙar muhimmanci a rayuwa.
• Da haƙuri ne mumini zai jure wa duk wani raɗaɗi, zai guji raki, zai rungumi nauyin da'awa da aikin alheri da ya hau kansa, zai miƙa wuya ga umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Da gaskiya ne mumini yake samun ɗaukaka, domin ƙarya rauni ce, kasa faɗar gaskiya ma rauni ne.
• Da ɗa'a ga Allah ne mumini zai zo da haƙƙin Allah na bauta masa shi kaɗai, kuma ya tsare matsayinsa na shi bawan Allah ne, ba bawan wani ba.
• Da ciyarwa mumini zai 'yanta kansa daga bauta wa kuɗi da ƙarantar rowa, ya haɓaka alaƙa ta mutuntaka tsakanin mutum da mutum.

6. Allah ya kinsa wa namiji son haihuwar ɗa namiji. Yakan yi farin ciki da samun sa, da kuma alfahari da yawan 'ya'ya maza.

7. Halaccin yin tawassuli da imanin mutum da Allah da sauran rukunan imani. Wannan yana ƙarƙashin tawassuli da ayyuka na ƙwarai.

Suratu Ali-Imran (14-17)

زُيِّنَ لِلنَّاسِ حُبُّ ٱلشَّهَوَٰتِ مِنَ ٱلنِّسَآءِ وَٱلْبَنِينَ وَٱلْقَنَٰطِيرِ ٱلْمُقَنطَرَةِ مِنَ ٱلذَّهَبِ وَٱلْفِضَّةِ وَٱلْخَيْلِ ٱلْمُسَوَّمَةِ وَٱلْأَنْعَٰمِ وَٱلْحَرْثِ ۗ ذَٰلِكَ مَتَٰعُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ وَٱللَّهُ عِندَهُۥ حُسْنُ ٱلْمَـَٔابِ ﴿١٤﴾ ۞ قُلْ أَؤُنَبِّئُكُم بِخَيْرٍ مِّن ذَٰلِكُمْ ۖ لِلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّٰتٌ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَأَزْوَٰجٌ مُّطَهَّرَةٌ وَرِضْوَٰنٌ مِّنَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِٱلْعِبَادِ ﴿١٥﴾ ٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَآ إِنَّنَآ ءَامَنَّا فَٱغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَا وَقِنَا عَذَابَ ٱلنَّارِ ﴿١٦﴾ ٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلْقَٰنِتِينَ وَٱلْمُنفِقِينَ وَٱلْمُسْتَغْفِرِينَ بِٱلْأَسْحَارِ ﴿١٧﴾

14. An ƙawata wa mutane son sha’awace-sha’awace na mata da 'ya'ya da dukiya mai yawa abar tarawa ta zinariya da azurfa da kuma kiwatattun dawaki da dabbobi na gida da amfanin gona. Waɗannan duk morewa ce ta rayuwar duniya; Allah kuwa a wurinsa ne kyakkyawar makoma take.
15. Ka ce: "Shin in ba ku labarin da abin da ya fi waɗancan alheri? Waɗanda suka yi taƙawa, suna da wasu aljannatai waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, a wurin Ubangijinsu, suna masu zama a cikinsu dindindin da mata na aure tsarkaka da kuma yarda daga Allah. Kuma Allah Yana ganin bayinsa."

16. Su ne waɗanda suke cewa: "Ya Ubangijinmu, lalle mu mun yi imani, don haka Ka gafarta mana zunubanmu, kuma Ka tserar da mu daga azabar wuta.”

17. (Su ne) masu haƙuri, masu gaskiya, kuma masu ɗa'a, kuma masu ciyarwa, kuma masu neman gafara lokacin sahur.

Bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a baya ya nuna cewa, dukiya da ‘ya’ya ba za su amfani waɗanda suka kafirce masa ba, sai kuma a waɗannan ayoyin yake gargaɗi ga waɗanda ƙyale-ƙyalin rayuwar duniya za su shagaltar da su, har su manta da lahira. Allah ya bayyana cewa, ya sanya wa mutane son wasu abubuwa na sha’awa, kamar mata da ‘ya’ya maza da tara nau’ukan dukiyoyi iri-iri, kamar zinare da azurfa, da kiwatattun dawakai da raƙuma da shanu da ƙananan dabbobi da gonakin noma. Allah ya bayyana duk waɗannan abubuwan na more daɗin duniya ne, daga ƙarshe su tafi su bar su, kuma a wurin Allah kaɗai ake samun kyakkyawar makoma da sakamako mai yawa marar yankewa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana wa Annabinsa (ﷺ) cewa, akwai abin da ya fi waɗannan ƙyale-ƙyali kayan sha’awar na duniya a wurin Allah, waɗanda su ne aljannatai na ni’ima, da abin da yake cikinsu na gidaje manya-manya, waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, ga kuma tsarkakan mata a cikinsu. Kuma wannan ni’imar ta har abada ce, ba mai yankewa ba, za su yi ta zama a cikinta har abada. Tare da waɗannan ni’imomi kuma akwai wata babbar ni’ima, wadda ta zarce kowace ni’ima girma, ita ce samun yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Abu Sa’id Alkhudri (Allah ya kara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah Ta’ala zai ce wa ‘yan Aljanna: “Ya ku ‘yan Aljanna.” Sai su ce: “Mun amsa maka, ya Ubangijinmu.” Sai ya ce: “Shin kun yarda?” Sai su ce: “Me zai sa ba za mu yarda ba, alhalin ka ba mu abin da babu wanda ka taɓa ba shi irinsa a cikin halittarka?” Sai Allah ya ce: “To zan ba ku abin da ya fi wannan da na ba ku.” Sai su ce: “Ya Ubangiji, mene ne kuma ya fi wannan da ka ba mu?” Sai ya ce: “Zan halatta muku yardata, daga yanzu ba zan yi fushi da ku ba har abada.” [Bukhari #6549, da Muslim #2829].

Kuma Allah mai ganin duk bayinsa ne, muminai da kafirai, da mutanen kirki da na banza, yana sane da halin da kowannensu yake ciki, don haka mai yi musu sakayya ne a kan ayyukansu kyawawa da munana. Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci waɗanda suka cancanci samun waccan ni’ima da ya ambata ta lahira. Ya nuna cewa, su ne masu kamun-ƙafa a wurinsa da imanin da suka yi da shi, da littafinsa da Manzonsa, suna roƙon sa da ya yi musu baiwar gafarar zunubansu, ya kuma tsare su shiga azabar wuta. Sannan ya ƙara ambatar wasu siffofin nasu da cewa, su masu haƙuri ne, wajen aikata ɗa’a da barin saɓon Allah, da haƙuri a kan ƙaddara marar daɗi, kuma masu gaskiya ne a maganganunsu da ayyukansu, masu ɗa’a ne ga Allah, masu ciyar da dukiyoyinsu don Allah a duk inda ya zama wajibi, ko ta hanyar neman lada, sannan masu neman gafarar Allah ne a ƙarshen dare.
An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ubangijinmu Tabaraka wa Ta’ala yana sauka a sama ta kusa a kowane dare, yayin da sulusin ƙarshe na daren ya yi saura, yana cewa: “Wane ne zai roƙe ni, in amsa masa, wane ne zai tambaye ni, in
ba shi, wane ne zai nemi gafarata, in gafarta masa?” [Bukhari #1145, Muslim #758].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman lamarin Tauhidi, ta yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi da kansa ne yake ba da shaida a kai.

2. Bayanin falalar mala'iku, ta yadda Allah ya ambace su a matsayin mataki na biyu bayansa.

3. Falalar malamai ta fuskoki daban-daban kamar haka:
• Allah ya ware su su zama shaida a kan wani babban al'amari, wanda shi ne Tauhidi.
• Allah ya haɗa shaidarsa tare da shaidarsu da ta mala'iku.
• Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo su da sunan 'masu ilimi', wanda hakan yake nuna cewa, lalle sun siffantu da wannan sifa ta ilimi.
• Allah ya zaɓe su suka zama masu shaida, kuma hujja a kan sauran mutane, dole sauran mutane su yi aiki da hujjar da suka bayar, sai ya zamanto duk wanda ya yi aiki da wannan abu da suka yi shaida a kansa; to suna da kamasho na lada a wurin Allah.
• Zaɓo su da Allah ya yi su zamanto masu ba da shaida yana nuna cewa su a wurinsa adalai ne, ba abin suka ba ne, don ba a kafa shaida sai da adali.

Suratu Ali-Imran (18)

شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَأُو۟لُوا۟ ٱلْعِلْمِ قَآئِمًۢا بِٱلْقِسْطِ ۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١٨﴾

18. Allah Ya shaida cewa, babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi, haka mala'iku ma da ma'abota ilimi, Tsayayye ne da adalci. Babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi, Mabuwayi, Mai hikima.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi bayinsa muminai, sai kuma ya ambaci dalilai na zahiri masu ƙarfi, waɗanda suke tabbatar da kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Waɗannan dalilai su ne; shaidar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), inda ya ba da shaidar cewa, babu abin bauta wa da gaskiya sai shi. Sannan ya biyo ta da shaidar mala'ikunsa da ta malamai a cikin bayinsa, wanda kuma shi yake tsaye da adalci cikin dukkanin lamura da kuma dukkan ayyukansa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sake tabbatar da wajabcin a bauta masa shi kaɗai, ba tare da an haɗa shi da abokin tarayya ba. Ya kuma bayyana cewa, shi Mabuwayi ne, ba wanda zai iya ja da shi, ko ya gagare shi, kuma Mai hikima ne a cikin duk maganganunsa da ayyukansa.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Musulunci ne kaɗai addinin da Allah ya yarda a bauta masa da shi, domin shi ne addinin annabawa gaba ɗayansu.

2. Rashin adalci shi ne babban abin da yake haifar da saɓani da rikici tsakanin al'umma.

3. Duk mutumin da yake jayayya da kai, ba don ku fahimci gaskiya ba kai da shi, sai don ya tabbatar da son zuciyarsa; to ka rabu da shi, domin jayayya da shi ba ta da sauran amfani.

4. Ci gaba da saɓani bayan bayyanar ilimi da tsayuwar hujja abu ne mai munin gaske.

5. Shiriya tana da yanayi da kamanni ne iri ɗaya, shi ne haƙiƙanin Musulunci; duk wani abu ba wannan ba; to ɓata ne ba shiriya ba.

Suratu Ali-Imran (19-20)

إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلۡإِسۡلَٰمُۗ وَمَا ٱخۡتَلَفَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡعِلۡمُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۗ وَمَن يَكۡفُرۡ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٩ فَإِنۡ حَآجُّوكَ فَقُلۡ أَسۡلَمۡتُ وَجۡهِيَ لِلَّهِ وَمَنِ ٱتَّبَعَنِۗ وَقُل لِّلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡأُمِّيِّـۧنَ ءَأَسۡلَمۡتُمۡۚ فَإِنۡ أَسۡلَمُواْ فَقَدِ ٱهۡتَدَواْۖ وَّإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا عَلَيۡكَ ٱلۡبَلَٰغُۗ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِٱلۡعِبَادِ ٢٠

19. Lalle addini a wurin Allah shi ne Musulunci. Kuma waɗanda aka ba wa Littafi ba su yi saɓani ba sai bayan da ilimi ya zo musu saboda zalunci a tsakaninsu. Wanda kuwa duk ya kafirce wa ayoyin Allah, to lalle Allah Mai gaggawar hisabi ne.

20. To idan sun yi jayayya da kai, sai ka ce: “Ni na miƙa wuyana ne ga Allah, haka ma wanda ya bi ni.” Kuma ka faɗa wa waɗanda aka bai wa Littafi da Ummiyyai: "Shin kun miƙa wuya?" To idan sun miƙa wuya, haƙiƙa sun shiryu; idan kuwa suka juya baya, to babu abin da yake a kanka sai isar da saƙo. Kuma Allah Shi ne Mai ganin bayinsa.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi kaɗai ne ya cancanta a bauta masa, sai kuma ya zo da bayani a kan addinin da za a bauta masa da shi. Allah ya tabbatar da cewa, lalle addinin gaskiya, kuma karɓaɓɓe a wurin Allah, shi ne Musulunci, Allah ba zai yarda a bauta masa da wani addinin ba Musulunci ba. Sannan ya bayyana dalilin saɓanin ma’abota littafi da cewa, ya faru ne bayan an tsayar musu da hujja ta hanyar aiko musu da annabawa da saukar musu da littattafai, kuma abin da ya kai su ga sassaɓawa shi ne zalunci da ƙetare haddi da ya riƙa faruwa a tsakaninsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo batun sakamakon wanda ya kafirce wa ayoyinsa da cewa, Allah zai yi masa hisabi a kan wannan, cikin gaggawa, zai lissafa dukkan ayyukan bayinsa ba tare da buƙatar amfani da wata na’ura ta lissafi ba, kuma duk yawansu a lokaci guda, a kuma wuri guda, a ɗan taƙaitaccen lokaci. Sannan ita kanta ranar hisabin dab take da zuwa, domin rayuwar duniya gajeriya ce.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karkatar da akalar magana zuwa ga Annabinsa (ﷺ) cewa, idan kafirai sun yi jayayya da shi a kan gaskiyar da ya zo musu da ita, to ya fito ya faɗa musu cewa, shi dai yana yin aikinsa ne don Allah shi kaɗai, hakanan ma duk wanda ya bi shi yana aikinsa ne ga Allah shi kaɗai. Ya kuma umarce shi da ya fito ya faɗa wa Yahudawa da Nasara waɗanda Allah ya ba su littafi da kuma mushirikai waɗanda ba su da wani littafi: Shin sun miƙa wuya ga Allah, kuma za su bauta masa shi kaɗai? Idan sun miƙa wuya kamar yadda su Musulmi suka miƙa wuya, to sun shiryu, sun hau turbar gaskiya. Idan kuwa suka bijire wa wannan kira da ake yi musu, to ba wani laifi a kan shi Ma’aiki, domin isar da saƙo ne kawai aikinsa. Allah yana ganin duk bayinsa, ya san wanda zai karɓi shiriya da wanda ba zai karɓa ba, kuma makomar kowa ga Allah take, zai yi wa kowa hisabi bisa aikinsa na alheri ko na sharri.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Waɗanda suke kafirce wa ayoyin Allah, kuma suke kashe annabawa da masu wa’azi, Allah ya haɗa musu azaba iri uku:
• Haɗa su da ɓacin rai da ciwon damuwa, don haka ya ce: “Yi musu albishir da wata azaba mai raɗaɗi.”
• Rushewar duk wani abu mai amfani a gare su a duniya da lahira gaba ɗaya.
• Rashin mai taimako ko agaji a gare su.

2. Kasancewar sun saɓa wa Allah ta fuskoki uku, sai ukubarsu ma ta zama iri uku:
• Sun kafirce wa ayoyin Allah, sai ya ce a yi musu albishir da azaba mai raɗaɗi.

• Sun kashe annabawa, sai Allah ya rushe ɗaukacin ayyukansu na alheri, ba za su yi musu amfani ba duniya da lahira.
• Sun kashe malamai masu wa'azi, sai Allah ya hana musu samun masu taimakon su yayin da azabar Allah ta zo musu, kamar yadda waɗannan malamai suka rasa masu taimakon su lokacin da aka zo kashe su.

3. Malamai masu wa'azi su suke biye da annabawa wajen martaba a wajen Allah.

Suratu Ali-Imran (21-22)
إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقۡتُلُونَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ بِغَيۡرِ حَقّٖ وَيَقۡتُلُونَ ٱلَّذِينَ يَأۡمُرُونَ بِٱلۡقِسۡطِ مِنَ ٱلنَّاسِ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٢١ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ حَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٢٢

21. Lalle waɗanda suke kafirce wa ayoyin Allah, kuma suke kashe annabawa ba tare da wani haƙƙi ba, kuma suke kashe waɗanda suke yin umarni da adalci cikin mutane, to ka yi musu albishir da wata azaba mai raɗaɗi.

22. Waɗannan su ne waɗanda ayyukansu suka lalace a duniya da lahira, kuma ba su da wasu mataimaka.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin waɗanda suka kafirce wa ayoyinsa cewa, ba a nan suka tsaya ba; sun ci gaba da kutsawa cikin shisshiginsu da kafircinsu, har suka kai ga kashe wasu annabawa da manzanni, ba tare da sun yi musu wani laifi ba. Hakanan suka riƙa kashe bayin Allah nagari masu yin umarni da a yi adalci, kuma a yi kyakkyawan aiki, suke hana mummuna. Kashe irin waɗannan bayin Allah shi ne ƙololuwar girman kai, kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Girman kai shi ne watsi da gaskiya da wulaƙanta mutane." [Muslim #91].
Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa (ﷺ), da ya yi musu albishir da wata azaba mai raɗaɗi, sakamakon kafircinsu da miyagun ayyukansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ayyukan waɗannan mutane duk sun rushe, sun lalace, ba abin da zai amfane su a duniya ko a lahira, kuma har ila yau ba za su sami mai taimakon su ba, wanda zai kuɓutar da su daga azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah yana iya ba wa bawansa ilimi, amma kuma ya rasa samun dacen aiki da ilimin.

2. Wajibi ne Musulmi ya yi hattara ya bar guje wa aiki da hukuncin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Dole ya saurara, kuma ya bi, ya sallama.

3. Burace-burace mummunar ɗabi'a ce da take jawo wa mutum ya yarda da abin da ba gaskiya ne ba, ya saki aiki da gaskiya.

4. Mutum duk sanda ya riƙa ganin shi ba za a saka shi a wuta ba, har ya kai ga ƙudurce hakan, wannan yana iya kai shi ga tsaurin idon keta dokar Allah da bijire wa gaskiya.

5. Ruɗuwa da yawan aiki na ƙwarai alama ce ta ƙarancin hangen nesa, domin ba wai mutum ya yi aikin ba ne muhimmi; muhimmin abu shi ne Allah ya karɓi aikinsa. Domin akwai wanda aikinsa na wahala ne kaɗai, saboda bai cika sharaɗin karɓuwarsa ba ko kuma ya haɗa shi da abin da zai lalata shi.

Suratu Ali-Imran (23-25)

أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ أُوتُواْ نَصِيبًا مِّنَ ٱلْكِتَٰبِ يُدْعَوْنَ إِلَىٰ كِتَٰبِ ٱللَّهِ لِيَحْكُمَ بَيْنَهُمْ ثُمَّ يَتَوَلَّىٰ فَرِيقٌ مِّنْهُمْ وَهُم مُّعْرِضُونَ ﴿٢٣﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَالُواْ لَن تَمَسَّنَا ٱلنَّارُ إِلَّآ أَيَّامًا مَّعْدُودَٰتٍ ۖ وَغَرَّهُمْ فِى دِينِهِم مَّا كَانُواْ يَفْتَرُونَ ﴿٢٤﴾ فَكَيْفَ إِذَا جَمَعْنَٰهُمْ لِيَوْمٍ لَّا رَيْبَ فِيهِ ۖ وَوُفِّيَتْ كُلُّ نَفْسٍ مَّا كَسَبَتْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿٢٥﴾

23. Shin ba ka ga waɗannan da aka ba su wani kaso na ilimin Littafi ba, ana kiran su zuwa ga Littafin Allah don Ya yi hukunci a tsakaninsu, sannan sai wani ɓangare daga cikinsu suna juya baya, suna masu bijirewa.

24. Wannan kuwa saboda su sun ce: "Wuta ba za ta shafe mu ba sai a waɗansu ‘yan kwanaki ƙididdigaggu." kuma abin da suka kasance suna ƙirƙira a addininsu shi ne ya ruɗe su.

25. To yaya halinsu zai kasance idan Muka tara su a wani yini da babu shakka game da shi, kuma kowane rai za a saka masa da abin da ya aikata, kuma su ba za a zalunce su ba?

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin waɗanda aka ba su wani kaso na ilimin littafin da Allah ya saukar, su ne Yahudawa cewa, lokacin da ake kiran su su zo ga hukuncin littafin da suka yi imani da shi, suka yarda da abin da yake cikinsa cewa daga Allah yake, sai wasu daga cikinsu suka riƙa bijirewa, suna goce wa hukuncin wannan littafin. Kuma abin da ya jawo har suka yi haka shi ne ƙaryar da suka yarda da ita na cewa, Allah ba zai yi musu azaba ba, sai ta ‘yan kwanaki kaɗan ƙididdigaggu, sai ya fito da su. To wannan ƙaryar ce ta ruɗe su a addininsu, har ma suke ganin cewa, suna iya saba wa hukuncin Allah, ko su bijire masa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Yahudawa sun je wurin Annabi (ﷺ) suka faɗa masa cewa wani namiji da wata mata daga cikinsu sun yi zina, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce musu: “Me kuka sani a cikin littafin Attaura dangane da jefe mazinata?” Sai suka ce: “Ai kunyata su muke yi, kuma a yi musu bulala.” Sai Abdullahi ɗan Salam ya ce: “Karya kuke yi, a cikin Attaura akwai ayar hukuncin jefe mazinaci.” Sai suka ɗauko Attaurah suka buɗe ta, sai ɗaya daga cikinsu ya sa hannunsa ya danne ayar jefewa, ya riƙa karanta abin da yake gabanta, da abin da yake bayanta. Sai Abdullahi ɗan Salam ya ce: “Cire hannunka!” Yana cire hannunsa, sai ga ayar, sai kuma dukansu suka ce: “E, gaskiya ya faɗa, ya Muhammadu, akwai ayar jefe mazinaci a cikin Attaura.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce a je a jefe su. Aka jefe su.” [Bukhari #3635, da Muslim #1699].

Dangane da batun Yahudawa na cewa ba za a sa su wuta ba sai na ‘yan kwanaki kaɗan, Abu Hurairah (Allah ya kara masa yarda) ya ruwaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya tambayi Yahudawa: “Su wane ne ‘yan wuta?” Sai suka ce: “Za mu shiga wuta na wani ɗan lokaci kaɗan, sannan sai a cire mu, a sa ku a madadinmu.” Sai Annabi (ﷺ) ya ce musu: “Ku yi mana shiru, wallahi har abada ba za mu maye gurbinku a cikinta ba.” [Bukhari #3169].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar da su azabar ranar da za a tattaro su gaba ɗayansu, yana mai cewa, yaya halinsu zai kasance tare da waɗannan miyagun ayyuka nasu, lokacin da za a zartar da hukunci a tsakaninsu, ranar da babu kokwanto a zuwanta, ita ce ranar alƙiyama? A wannan rana za a cika wa kowane rai sakamakon aikinsa na alheri ko na sharri, babu wanda za a zalunta ta hanyar a tauye masa ladansa ko a ƙara masa laifin da ba shi ya yi ba ko a hukunta shi da laifin wani. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa a hadisi Kudusi: “Ya ku bayina, ni na haramta wa kaina zalunci....” [Muslim #2577].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mulki gaba ɗaya na Allah ne, a wurinsa ne ya kamata a nema, ba a wurin wani, ko wasu ba.

2. Don Allah ya ba wa mutum mulki ba shi yake nuna ya ɗaukaka shi ba. Zai iya ba shi mulki, amma ya zama a ƙaskance, wasu ne suke sarrafa shi yadda suke so. Ko kuma Allah ya hana masa ikon tafiyar da mulkin da siyasar al'ummarsa, don haka ya rayu cikin rauni da gazawa. Kamar yadda rashin samun mulki ba ya nuna ƙaskanci, Allah yakan ɗaukaka wanda ya ga dama ta wasu hanyoyi daban, ba sai ta hanyar mulki ba.

3. Duk alheri a hannun Allah yake shi kaɗai, don haka ka nema a wurinsa.

4. Allah ne mai ba da arziki, shi ne mai hanawa, don haka bawa ya nema a wajensa, zai samu.

5. Duk aikin Allah alheri ne, don haka ba a jingina masa sharri, kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Alheri duka yana hannunka, kuma ba a jingina maka sharri." [Muslim #771].

Suratu Ali-Imran (26-27)

قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلۡمُلۡكِ تُؤۡتِي ٱلۡمُلۡكَ مَن تَشَآءُ وَتَنزِعُ ٱلۡمُلۡكَ مِمَّن تَشَآءُ وَتُعِزُّ مَن تَشَآءُ وَتُذِلُّ مَن تَشَآءُۖ بِيَدِكَ ٱلۡخَيۡرُۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٦ تُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي ٱلنَّهَارِ وَتُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِۖ وَتُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَتُخۡرِجُ ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّۖ وَتَرۡزُقُ مَن تَشَآءُ بِغَيۡرِ حِسَابٖ ٢٧

26. Ka ce: "Ya Allah, Kai ne Mamallakin mulki, Kana bayar da mulki ga wanda Ka ga dama, kuma Kana ƙwace mulki daga wanda Ka ga dama, kuma Kana ɗaukaka wanda Ka ga dama, kuma Kana ƙaskantar da wanda Ka ga dama; duk alheri yana hannuka, lalle Kai Mai iko ne a kan komai.

27. "Kana shigar da dare a cikin yini, kuma Kana shigar da yini a cikin dare, kuma Kana fitar da mai rai daga cikin matacce, kuma Kana fitar da matacce daga cikin mai rai; kuma Kana arzurta wanda Ka ga dama ba tare da lissafi ba."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabinsa (ﷺ) da ya roƙe shi, ya girmama sunansa, ya ce: Ya Allah wanda mulkin komai naka ne, kai ne Mamallakin duniya da lahira da duk abin da yake cikinsu, kai kake bayar da mulki ga wanda ka ga dama ka kuma ƙwace mulki daga wanda ka ga dama; kana ɗaukaka wanda ka ga dama ta hanyar hore masa aikin ɗa'a gare ka ko ta hanyar ba shi mulki da iko ko ka ba shi nasara ko wanin haka. Kuma kana ƙaskantar da wanda ka ga dama ta hanyar ya zama mai saba maka ko ta hanyar ƙwace mulkinsa ko ɗora maƙiyansa a kansa, ko makamancin haka. Alheri duka yana hannunka. Lalle Allah kai mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare ka aiwatarwa idan ka ga damar aiwatar da shi.
Yana daga cikin cikakken ikonka ya Allah, ka shigar da dare a cikin yini, kuma ka shigar da yini a cikin dare, watau ka sanya wasu sa'o'in dare a cikin sa'o'in yini, ko wasu sa'o'in yini ka ƙara su a kan sa'o'in dare. Kuma kana fitar da mai rai daga matacce, kamar fitar da mutum ko dabba mai rai daga ruwan maniyyi ko ka fitar da shuka daga ƙwayar iri ko kaza daga ƙwai ko kuma ka fitar da mumini daga kafiri. Hakanan kuma kana fitar da matacce daga mai rai, kamar fitar da ruwan maniyyi daga mutum ko dabba mai rai, ko ka fitar da ƙwaya daga shuka ko ka fitar da ƙwai daga kaza ko ka fitar da kafiri daga tsatson mumini. Kuma kana arzuta wanda ka ga dama cikin bayinka da arziki mai yawa, ba tare da ƙuntata masa ba.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba a shugabantar da wanda ba Musulmi ba a kan al'umma ta Musulmi.

2. Ba ya halatta ga mumini ya ƙudurce ƙauna da soyayya ta addini ga wanda ba Musulmi ba. Amma ƙauna ta ɗabi'a, kamar irin ta ɗa da mahaifi, ko miji da mata, wannan babu komai, matuƙar ba ta kai ga taimaka musu ba kan cutar da Musulmi ko fifita su a kan musulmai.

3. 'Taƙiyya' tana kasancewa ne tsakanin muminai da kafirai, ba a tsakanin musulmai ba, kamar yadda mabiya addinin Shi'a suka ɗauka.

Suratu Ali-Imran (28)

لَّا يَتَّخِذِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلۡكَٰفِرِينَ أَوۡلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۖ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ فَلَيۡسَ مِنَ ٱللَّهِ فِي شَيۡءٍ إِلَّآ أَن تَتَّقُواْ مِنۡهُمۡ تُقَىٰةٗۗ وَيُحَذِّرُكُمُ ٱللَّهُ نَفۡسَهُۥۗ وَإِلَى ٱللَّهِ ٱلۡمَصِيرُ ٢٨

28. Kada muminai su riƙi kafirai a matsayin masoya su ƙyale muminai; wanda kuwa duk ya aikata haka, to shi ba komai ne ba a wurin Allah, sai dai in don ku kare kanku ne daga gare su. Kuma Allah Yana tsoratar da ku kansa. Kuma zuwa ga Allah makoma take.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana muminai su riƙi kafirai masoyansu, watau majiɓinta al'amuransu, suna taimakon su, su yi watsi da 'yan'uwansu muminai. Allah ya bayyana cewa, duk wanda ya yi haka; to babu ruwan Allah da shi. Amma kuma sai Allah ya yi togaciyar lokacin da ake tsoron wani sharrin nasu, to a wannan lokaci za a iya nuna musu ƙauna da baki, ba da zuciya ɗaya ba, ba kuma tare da taimakon su a kan kafircinsu ko taya su aikata saɓon Allah ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi muminai game da kansa, watau kada su aikata abin da zai jawo musu fushinsa, yana mai bayyana musu cewa, makomarsu gaba ɗaya zuwa gare shi ne, kuma zai yi musu hisabi a kan ayyukansu.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga tsarkake zukata daga aikata zunubi da halarto da ilimin Allah a ko da yaushe, don bawa ya riƙa jin kunyar Ubangijinsa, wanda yake ganin ko'ina a zuciyarsa.

2. Duk sa'adda mumini ya yi imani da sifar ilimi ta Ubangijinsa, wannan zai gadar masa abubuwa guda biyu:
• Zai guje wa saɓon Allah, ba zai yarda Allah ya gan shi a wurin da ya hana shi ba.
• Zai yi kwaɗayin biyayya ga Allah, ba zai yarda Allah ya rasa shi a wurin da ya umarce shi ba.

3. Tuna wa bawa ranar lahira da girman tsorace-tsoracenta, domin abin da bawa ya aikata sai an kawo masa shi a gabansa, an yi masa hisabi a kansa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo wa'azin da yake yi wa muminai a wannan ayar da suna 'gargaɗi', watau kashedi, domin ana gargaɗi ga wanda bai riga ya auka cikin haɗari ba, domin a hana shi aukawa cikinsa.

5. Allah ya rufe wannan gargaɗi nasa da faɗarsa: “Allah mai jin ƙan bayi ne,” domin yi wa mutum bayanin yadda lamari yake, yana daga cikin nau’i na tausaya masa.

Suratu Ali-Imran (29-30)

قُلْ إِن تُخْفُواْ مَا فِي صُدُورِكُمْ أَوْ تُبْدُوهُ يَعْلَمْهُ ٱللَّهُۗ وَيَعْلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلْأَرْضِۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ٢٩ يَوْمَ تَجِدُ كُلُّ نَفْسٍ مَّا عَمِلَتْ مِنْ خَيْرٍ مُّحْضَرًا وَمَا عَمِلَتْ مِن سُوٓءٍ تَوَدُّ لَوْ أَنَّ بَيْنَهَا وَبَيْنَهُۥٓ أَمَدًۢا بَعِيدًاۗ وَيُحَذِّرُكُمُ ٱللَّهُ نَفْسَهُۥۗ وَٱللَّهُ رَءُوفٌۢ بِٱلْعِبَادِ ٣٠

29. Ka ce: “In za ku ɓoye abin da yake cikin ƙirazanku ko kuma ku bayyana shi, Allah Ya san shi, kuma Yana sane da abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai.”

30. Ranar da kowane rai zai sami abin da ya aikata na alheri an halarto da shi, abin da kuwa ya aikata na mummunan aiki, zai so ina ma da a ce tsakaninsa da shi akwai wata tazara mai nisa. Kuma Allah Yana tsoratar da ku kansa, kuma Allah Mai tausayi ne ga bayi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Manzonsa da ya faɗa wa muminai cewa, ko da za su ɓoye abin da yake cikin zukatansu na alheri ko na sharri, na soyayya ko na ƙiyayya, ko kuma su bayyana hakan a maganganunsu ko ayyukansu; to Allah ya san da hakan, kuma zai yi musu sakayya a kai; wanda ya shuka alheri ya girbi alheri; wanda kuma ya shuka sharri ya girbi sharri. Allah shi ne wanda iliminsa ya kewaye da duk abin da yake sama da abin da yake ƙasa, babu abin da yake ɓoye masa, kuma yana da cikakken iko a kan komai, babu abin da zai gagare shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana lokacin wannan sakayyar, watau ranar alƙiyama, ranar da kowane rai zai ga abin da ya aikata, kaɗan ne ko mai yawa, an kawo masa shi cikakke, ba tare da tawaya ba, ko wani canji. To amma abin da mutum ya aikata na sharri, zai riƙa burin ina ma akwai tazara mai nisa a tsakaninsa da mummunan aikinsa. Sai kuma Allah ya sake jaddada tsoratarwarsa da gargaɗinsa game da kansa, yana mai bayyana cewa, yana yi musu wannan gargaɗin ne saboda shi mai yawan rahama ne gare su, mai yawan jin ƙai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dole ne mumini ya bi Manzon Allah (ﷺ) cikin duk al’amuran rayuwarsa, tun daga aƙida da shari’a da mu’amala, har zuwa ɗabi’u da halaye, a ayyukansa da maganganunsa.

2. Son Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba kawai cika-baki ba ne ko burga; tsayawa ne ƙyam a kan sunnar Manzon Allah (ﷺ) da bin sa sau da ƙafa. Wanda ya yi haka kuwa shi ne masoyin Allah, kuma waliyyinsa na gaskiya; wanda kuma ya saɓa haka; to wannan ya tabbata maƙaryaci, kuma waliyyin Shaiɗan.

3. Wannan ayar tana ƙarya lagon duk wani mai cika-baki da nuna soyayya ga Allah ko ga Manzon Allah (ﷺ) bisa ga ƙarya, domin wannan jarrabawa ce a gare shi, idan ya ci jarrabawa; to ya shiga tsarin masoya na gaskiya, idan kuwa ya faɗi jarrabawar; to cika-bakinsa ba zai tsinana masa komai ba.

4. Yin biyayya ga masoyi alama ce mai nuna gaskiyar soyayyarsa gare shi. Duk wanda ya so wani; to zai so abin da wannan masoyin nasa yake so.

5. A cikin waɗannan ayoyi akwai mayar da martani ga masu cewa, ba a aiki da sunna sai idan ta ƙunshi abin da Alƙur’ani ya zo da shi. Wato idan ta keɓanta da shar’anta wani hukunci; to ba za a karɓa ba. Wannan ayar ta tabbatar da yi wa Manzon Allah (ﷺ) ɗa’a tashi ta kansa, domin bayan ta yi umarni da

ɗa’ar Allah, sai kuma ta sake yin wani umarnin da ɗa’ar Manzon Allah (ﷺ). Da a ce ba a yi masa ɗa’a shi a karan-kansa, sai a cikin abin da ya zo a Alƙur’ani, to da ya zamanto umarni da yi masa ɗa’a a nan ba shi da wata fa’ida ke nan.
6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana saka wa bawansa da sakamako fiye da aikinsa, don haka a nan ya saka wa mai son sa da soyayyarsa, sannan ya ƙara masa da gafarta masa zunubansa.

Suratu Ali-Imran (31-32)
قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١ قُلۡ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَۖ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٣٢

31. Ka ce: "In kun kasance kuna son Allah, to ku yi mini biyayya, sai Allah Ya so ku, kuma Ya gafarta muku zunubanku. Kuma Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.”

32. Ka ce: “Ku yi ɗa'a ga Allah da Manzo; to in kuwa kuka juya baya, to lalle Allah ba Ya son kafirai.”

A waɗannan ayoyi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umarnin Annabinsa (ﷺ) da ya faɗa wa masu da’awar son Allah da baki, amma ayyukansu suna ƙaryata haka cewa, idan har da gaske suna son Allah, to alamar da za ta tabbatar da gaskiyar da’awarsu ita ce su bi Manzon Allah (ﷺ), su gaskata shi, su yi masa ɗa’a a kan abin da yake umarni da shi da abin da ya hana, domin son Allah da biyayya ga Manzon Allah (ﷺ) abubuwa ne da suke a haɗe ba sa rabuwa. To idan har wannan ya tabbata to a lokacin ne su ma Allah zai so su, kuma ya gafarta musu zunubansu, domin Allah mai gafarta zunubai ne, mai jin ƙai ga bayinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya umarce su da su tabbatar da haka; watau su yi wa Allah ɗa’a, kuma su yi wa Manzon Allah (ﷺ) ɗa’a; wannan kuwa shi zai fisshe su;, idan kuwa har suka bijire wa wannan umarni, to su san da sanin cewa sun kafirta, sun jefa kansu cikin fushin Allah, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya son kafirai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana zaɓen wasu daga cikin bayinsa, ya yi musu falala ta musamman, don su zama abin koyi cikin ayyukansu da maganganunsu da halayensu.

2. Ɗan’adam ba zai taɓa zama mai ‘yanci ba, har sai ya ‘yanta kansa daga bautar wani ba Allah ba, ya ‘yanta kansa daga bin koyarwar da ta saɓa da ta Allah, ya rungumi tsarin Allah gaba ɗaya a cikin dukkan al’amuran rayuwarsa.

3. Mutum ya riƙa neman ko da yaushe Allah ya karɓi aikinsa na ƙwarai, kada ya riƙa ruɗuwa da ayyukansa masu kyau, domin babban abin buƙata shi ne Allah ya karɓa daga gare shi.

4. Yana da kyau iyaye su riƙa yi wa ‘ya’yansu addu’a tun suna ciki da bayan haihuwarsu, su roƙa musu albarkar Ubangiji, su nema musu tsarinsa daga sharrin Shaiɗan.

5. Abin da Allah ya yi wa mahaifiyar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), na ba ta abinci da abin sha, ba tare da ta fita nema ba, karama ce da Allah ya gudanar a kanta, domin amsa addu’ar mahaifiyarta da kuma ya zama shimfiɗa ga abin da Allah yake niyyar zartar da shi na haihuwar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba tare da namiji ba.

6. Ba ya halatta wani ya kafa hujja da abin da ya faru ga Maryamu, ya zauna a masallaci ba ya fita neman abinci, yana jiran a kawo masa sadaka da sunan yana bauta wa Allah.
7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da bambanci tsakanin ɗa namiji da mace da faɗar mahaifiyar Maryamu: “Kuma ɗa namiji ba daidai yake da ‘ya mace ba.” Namiji da mace sun bambanta a ginin halittarsu da ɗabi’arsu da halayensu da mu’amalarsu, har ma da hukunce-hukuncensu a wasu lokuta.

8. Idan har za a ba wani riƙon yaro, to wajibi ne a danƙa shi ga wanda zai yi masa tarbiyya ta ƙwarai, domin ya taso cikin kamala da nagarta.9. Yana daga cikin rukunan godiya ga Allah bisa ni’imarsa, bawa ya yi iƙirari da cewa, wannan ni’imar da ya samu daga Allah take, ba yin kansa ba ne.

Suratu Ali-Imran (33-37)

*إِنَّ ٱللَّهَ ٱصۡطَفَىٰٓ ءَادَمَ وَنُوحٗا وَءَالَ إِبۡرَٰهِيمَ وَءَالَ عِمۡرَٰنَ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ٣٣ ذُرِّيَّةَۢ بَعۡضُهَا مِنۢ بَعۡضٖۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ٣٤ إِذۡ قَالَتِ ٱمۡرَأَتُ عِمۡرَٰنَ رَبِّ إِنِّي نَذَرۡتُ لَكَ مَا فِي بَطۡنِي مُحَرَّرٗا فَتَقَبَّلۡ مِنِّيٓۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٣٥ فَلَمَّا وَضَعَتۡهَا قَالَتۡ رَبِّ إِنِّي وَضَعۡتُهَآ أُنثَىٰ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا وَضَعَتۡ وَلَيۡسَ ٱلذَّكَرُ كَٱلۡأُنثَىٰۖ وَإِنِّي سَمَّيۡتُهَا مَرۡيَمَ وَإِنِّيٓ أُعِيذُهَا بِكَ وَذُرِّيَّتَهَا مِنَ ٱلشَّيۡطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ ٣٦ فَتَقَبَّلَهَا رَبُّهَا بِقَبُولٍ حَسَنٖ وَأَنۢبَتَهَا نَبَاتًا حَسَنٗا وَكَفَّلَهَا زَكَرِيَّاۖ كُلَّمَا دَخَلَ عَلَيۡهَا زَكَرِيَّا ٱلۡمِحۡرَابَ وَجَدَ عِندَهَا رِزۡقٗاۖ قَالَ يَٰمَرۡيَمُ أَنَّىٰ لَكِ هَٰذَاۖ قَالَتۡ هُوَ مِنۡ عِندِ ٱللَّهِۖ إِنَّ ٱللَّهَ يَرۡزُقُ مَن يَشَآءُ بِغَيۡرِ حِسَابٖ ٣٧

33. Lalle Allah Ya zaɓi Adamu, da Nuhu da iyalan gidan Ibrahimu da iyalan gidan Imrana Ya fifita su a kan sauran talikai.

34. Wata zurriya ce, sashinsu ‘ya’ya ne ga sashi. Kuma Allah Mai ji ne, Mai yawan sani.

35. Tuna lokacin da matar Imrana ta ce: “Ya Ubangijina, lalle ni na yi maka bakancen abin da yake cikina ya zamanto ‘yantacce, don haka Ka karɓa daga gare ni, lalle Kai ne Mai ji, Mai yawan sani.”

36. To yayin da ta haife ta sai ta ce: “Ya Ubangijina, lalle ni na haife ta ‘ya mace,” kuma Allah ne Ya fi sanin abin da ta haifa “Kuma ɗa namiji ba daidai yake da ‘ya mace ba; kuma lalle ni na raɗa mata suna Maryamu, kuma lalle ni ina nema mata tsarinka da zurriyarta daga Shaiɗan korarre.”

37. Sai Ubangijinta Ya karɓe ta da kyakkyawar karɓa, kuma Ya yi mata kyakkyawar tarbiyya, kuma Ya danƙa renonta a hannun Zakariyya; duk lokacin da Zakariyya ya shiga wurinta a ɗakin ibada, sai ya sami abinci a wurinta, sai ya ce: “Ya ke Maryamu, wannan daga ina kika samu?” Sai ta ce: “Wannan daga Allah ne; lalle Allah Yana arzurta wanda Ya ga dama ba tare da lissafi ba.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin irin zaɓin da ya yi a cikin bayinsa, watau ya zaɓi wasu ɗaiɗaikun mutane, ya kuma zaɓi wasu iyalai ya yi musu baiwa da falalarsa, ya fifita su a kan al’ummomin zamaninsu, ya ware su don bautar sa shi kaɗai. Cikin ɗaiɗaikun mutane Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zaɓi Annabi Adamu da Annabi Nuhu; a cikin gidaje ko iyali kuma, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zaɓi Annabi Ibrahimu da iyalinsa da Imrana da iyalinsa. Waɗannan zaɓaɓɓu Allah ya sanya nagarta da ayyukan ƙwarai a cikin zuriyyarsu. Allah shi ne mai cikakken ilimi game da wanda ya cancanci zaɓinsa a cikin bayinsa, domin shi ne mai ji, kuma mai cikakken sani.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin wasu ƙissoshi guda huɗu, masu ban mamaki wanda ya saba da yadda ɗan’adam ya saba gani.

Allah ya fara da ƙissar Maryam, mahaifiyar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), yadda ta kasance keɓantacciya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tun lokacin da mahaifiyarta ta ɗauki cikinta har ta haife ta, ta dimanci zama a wurin bautar Allah. Lokacin da mahaifiyarta ta ɗauki cikinta, ta yi wa Allah bakance cewa, abin da yake cikinta, za ta sadaukar da shi ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) don yi masa hidima a masallacin Baitul Maƙdis. Ta roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karɓi wannan bakance nata, domin shi mai jin addu'ar wanda ya roƙe shi ne, ya karɓa masa, kuma masani ne ga halin da kowane bawa yake ciki. To tana zaton abin da za ta haifa namiji ne; amma tana haihuwa, sai ta ga mace, sai take neman uzuri a wurin Allah, tana mai cewa, ga shi abin da ta haifa ya zamanto mace, ba namiji ba; mace kuma ba za ta iya yin abin da namiji zai iya ba na hidima da lazimtar wurin ibada a ko da yaushe, saboda raunin da take da shi da kuma larurar da take samun ta a duk wata, watau jinin al'ada. Sannan sai ta sanya wa 'yar tata suna Maryam, ta kuma roƙi Allah da ya tsare ta har da zuriyar da za ta haifa nan gaba, daga sharrin Shaiɗan la'ananne.

An karɓo daga Abu Hurairata (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Babu wani jariri da aka haifa, face sai da Shaiɗan ya shafe shi lokacin haihuwarsa, sai ku ji yaro ya fashe da kuka saboda shafar Shaiɗan, in ban da Maryam da ɗanta (Annabi Isa)." Sai Abu Huraira ya ce: "In kun ga dama ku karanta faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): "Lalle ni ina nema mata tsari da zuriyyarta daga Shaiɗan korarre." [Bukhari #3431, da Muslim #2366].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karɓi addu'arta, kuma ya karɓi wannan bakancen da ta yi, kyakkyawar karɓa, ya taso da Maryamu cikin kyakkyawar tarbiyya, mai ban sha'awa ga kowa, kuma Allah ya ɗora nauyin kula da tarbiyyarta a kan Zakariyya. To duk lokacin da Zakariyya ya kai mata ziyara wajen ibadarta, sai kawai ya tarar da abinci iri-iri a wurinta, sai abin ya riƙa ba shi mamaki, sai yake tambayar ta cewa, daga ina take samun abinci irin wannan? Sai ta amsa masa da cewa: "Daga wurin Allah ne, kuma shi Allah yana ba da arzikinsa ne ga wanda ya ga dama, ba tare da lissafi ba."

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk halittun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), har ma da annabawa, masu buƙata ne a wurin Allah, don haka shi kaɗai suke roƙa ya biya musu buƙatunsu.

2. Idan mutum zai roƙi Allah haihuwa; to ya roƙe shi zurriyya ta gari, domin ɗa nagari shi ne zai amfani mahaifansa duniya da lahira.

3. Yana da kyau idan mutum yana son biyan wata buƙata a wurin Allah; to ya yi riƙo da sabubban wannan buƙata, daga cikinsu akwai addu'a.

4. Yana da kyau mutum ya nemi abin da zai ƙara masa imani.

5. Yana da kyau idan mutum ya keɓanta, ya bar jama'a; to ya shagalta da yawan ambaton Allah da bautarsa.

6. Yi wa mutum albishir da samun wani alheri, kamar haihuwa.

Suratu Ali-Imran (38-41)

هُنَالِكَ دَعَا زَكَرِيَّا رَبَّهُۥ قَالَ رَبِّ هَبْ لِي مِن لَّدُنكَ ذُرِّيَّةً طَيِّبَةً ۖ إِنَّكَ سَمِيعُ ٱلدُّعَآءِ ﴿٣٨﴾ فَنَادَتْهُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَهُوَ قَآئِمٌ يُصَلِّي فِي ٱلْمِحْرَابِ أَنَّ ٱللَّهَ يُبَشِّرُكَ بِيَحْيَىٰ مُصَدِّقًۢا بِكَلِمَةٍ مِّنَ ٱللَّهِ وَسَيِّدًا وَحَصُورًا وَنَبِيًّا مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٣٩﴾ قَالَ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي غُلَٰمٌ وَقَدْ بَلَغَنِيَ ٱلْكِبَرُ وَٱمْرَأَتِي عَاقِرٌ ۖ قَالَ كَذَٰلِكَ ٱللَّهُ يَفْعَلُ مَا يَشَآءُ ﴿٤٠﴾ قَالَ رَبِّ ٱجْعَل لِّيٓ ءَايَةً ۚ قَالَ ءَايَتُكَ أَلَّا تُكَلِّمَ ٱلنَّاسَ ثَلَٰثَةَ أَيَّامٍ إِلَّا رَمْزًا ۗ وَٱذْكُر رَّبَّكَ كَثِيرًا وَسَبِّحْ بِٱلْعَشِيِّ وَٱلْإِبْكَٰرِ ﴿٤١﴾

38. A wannan lokacin sai Zakariyya ya roƙi Ubangijinsa, ya ce: “Ya Ubangijina, Ka ba ni zurriyya ta gari daga gare Ka, lalle Kai Mai amsa roƙo ne.”

39. Sai mala’iku suka kira shi, lokacin yana tsaye yana salla a cikin ɗakin ibada, (suka ce): “Lalle Allah Yana yi maka albishir da Yahaya, wanda yake mai gaskatawa da wata kalma daga Allah, kuma zai zama shugaba, kuma mai tsare kansa daga mata, kuma Annabi daga cikin salihan bayi.”

40. Ya ce: “Ya Ubangijina, ta yaya zan sami ɗa, ga shi tsufa ya riga ya cim mini, kuma ga shi matata juya ce?” Sai ya ce: “Kamar haka ne Allah Yake aikata abin da Ya ga dama.”

41. Ya ce: “Ya Ubangijina, Ka sanya mini wata alama.” Ya ce: “Alamarka ita ce ka kasa yi wa mutane magana yini uku sai dai da nuni. Kuma ka ambaci Ubangijinka ambato mai yawa, kuma ka yi tasbihi yammaci da safiya.”

Sai kuma a nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo ƙissa ta biyu, watau ƙissar Annabi Zakariyya, da yadda ya yi masa kyautar ɗa bayan har ya tsufa, ba tare da haihuwa ba, kuma ga shi matarsa bakarara, ba ta haihuwa.
Lokacin da Annabi Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ga irin karama da baiwar da Allah ya yi wa Maryamu sai shi ma ya ji son haihuwa ya dawo masa, ya sa rai ga samun biyan buƙatarsa, duk kuwa da halin da yake ciki na manyanta shi da matarsa. Sai ya ɗaga hannu ya yi addu’a yana cewa: “Ya Ubangijina, ka ba ni zurriyya ta gari daga gare ka, lalle kai mai amsa roƙo ne.” Sai ko Allah ya amsa masa addu’arsa, ya aiko wasu mala’iku don su yi masa albishir, suka same shi yana tsaye a masallaci yana salla, suka yi masa wannan albishir da cewa, zai haifi ɗa mai suna Yahya, wanda zai siffantu da siffofi masu girma, domin zai zama Shugaba wanda zai shugabanci mutanensa da halayensa na ƙwarai da iliminsa da addininsa, kuma mai ƙaurace wa mata da duk wani abu da zai tayar masa da sha’awa, mai shagala da bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sannan kuma zai zama Annabi daga cikin salihan bayi.
Yayin da Annabi Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ji wannan albishir na samun haihuwa, sai mamakin Kudurar Allah ya rufe shi, sai yake tambayar Allah, yana cewa: “Ya Ubangijina, ta yaya zan sami ɗa, alhalin ga shi ni na tsufa, na kai shekarun da ba zan iya haihuwa ba, sannan kuma ga matata bakarara ce da ma can ba mai haihuwa ba ce?” Sai Allah ya amsa masa da cewa, ai Allah yana aikata abin da ya ga dama ne. Daga nan sai Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nemi sanin wata alama da Allah zai nuna masa ta samun haihuwa, don ƙarin samun nutsuwar zuciya. Sai Allah ya sanar da shi cewa, alamar da zai gani ita ce, zai kasa magana da kowa har tsawon kwana uku, ba kuma don rashin lafiya, ko wani abu ya sami harshensa ba. Idan zai yi magana da mutane, sai dai ya riƙa nuni da hannunsa, amma kuma zai iya furta ambaton Allah a lokacin. Don haka Allah ya umarce shi da ya yi ta ambaton Ubangijinsa tare da tsarkake shi ta hanyar tasbihi da bautar sa yammaci da safiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar Maryam da fifikonta a kan sauran mata.

2. Allah ya ba da labarin tsarkinta don mayar da martani ga Yahudawa masu tuhumar ta game da haihuwar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

3. Idan Allah ya yi wa bawansa wata ni'ima; to yana daga cikin godiya ga Allah bawan ya yawaita ibada.

4. Annabi (ﷺ) bai san gaibu ba, sai abin da Allah ya sanar da shi ta hanyar wahayi.
5. Annabi (ﷺ) ya sami labarin Maryam daki-daki kamar haka, tare da cewa, shi ba mai karatu da rubutu ne ba, wani babban dalili ne da yake tabbatar da gaskiyar annabcinsa.

6. Halaccin yin ƙuri'a yayin da aka kasa warware wani saɓani.

Suratu Ali-Imran (42-44)

وَإِذْ قَالَتِ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَٰمَرْيَمُ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصْطَفَىٰكِ وَطَهَّرَكِ وَٱصْطَفَىٰكِ عَلَىٰ نِسَآءِ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٤٢﴾ يَٰمَرْيَمُ ٱقْنُتِى لِرَبِّكِ وَٱسْجُدِى وَٱرْكَعِى مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ﴿٤٣﴾ ذَٰلِكَ مِنْ أَنۢبَآءِ ٱلْغَيْبِ نُوحِيهِ إِلَيْكَ ۚ وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ يُلْقُونَ أَقْلَٰمَهُمْ أَيُّهُمْ يَكْفُلُ مَرْيَمَ وَمَا كُنتَ لَدَيْهِمْ إِذْ يَخْتَصِمُونَ ﴿٤٤﴾

42. Kuma ka tuna lokacin da mala'iku suka ce: "Ya ke Maryamu, lalle Allah Ya zaɓe ki, Ya kuma tsarkake ki, kuma Ya zaɓe ki a kan sauran mata na talikai.

43. "Ya ke Maryamu, ki yi ɗa'a ga Ubangijinki, kuma ki riƙa yin sujada, kuma ki riƙa yin ruku'u tare da masu ruku'u.

44. Wancan (abin da ya gabata a baya) yana cikin labaru na gaibi da Muke yi maka wahayinsa, kuma kai ba ka wurinsu lokacin da suka jefa alƙalumansu don tantance wane ne cikinsu zai karɓi renon Maryamu, kuma kai ba ka nan tare da su yayin da suke jayayya da juna.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana shimfiɗa ne game da ƙissa ta uku, wato ta Maryamu da ta haifi Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba tare da namiji ba. Allah ya yi shimfiɗa da bayanin zaɓin da ya yi wa Maryamu don ta zama ita ce wadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai gudanar da wannan al'amari nasa da ya saba wa al'adar da ɗan'adam ya saba gani, na halittar mutum daga haɗuwar ɗa namiji da 'ya mace. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabinsa labarin Maryamu lokacin da mala'iku suka kirawo ta, suna faɗa mata cewa, Allah ya zaɓe ta a cikin duka matan zamaninta, ya fifita ta a kansu, ya tsarkake ta da kyawawan halaye da riƙo da addini. Wannan zaɓin da aka yi mata, ba ƙaramar ni'ima ce gare ta ba, saboda haka akwai buƙatar ta yi wa Allah godiya a kai, ta tsarkake ɗa'arta ga Allah, ta zama mai bauta masa a ko da yaushe, kuma ta dinga yin salla tare da masallata. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa, waɗannan labarai da yake ba shi, na gaibu, waɗanda shi da mutanensa ba wanda ya san su, amma ga shi yanzu Allah ya sanar da shi su, don tabbatarr da shaida da dalili a kan gaskiyar annabcinsa, da ingancin wahayin da ya zo musu da shi. Allah ya ci gaba da faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, ba ya wurin lokacin da Annabi Zakariyya da sauran dangin Maryamu suka yi taro, suka tattauna batun wanda zai kula da rainonta, har ta kai su ga samun saɓani a tsakaninsu game da batun, har sai da aka yi ƙuri'a sannan aka zaɓi wanda zai riƙe ta, watau Annabi Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya gaya wa Annabinsa cewa wannan gaibu ne ya yi

masa wahayinsa; Allah kuwa shi ne ya kɓanta da sanin gaibu yake kuma sanar da wanda ya ga damar sanar da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alamar mai gaskiya ita ce maganganunsa da ayyukansa su riƙa yin daidai da na mutane masu gaskiya, kada su riƙa saɓawa da nasu ko da yaushe.

2. Yana daga cikin hikimar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wajen bayar da labarin abubuwan mamaki, ya fara da mafi ƙanƙantar abin mamaki, sannan wanda ya ɗara shi, sannan wanda yake gaba da shi, har a zo ga na ƙoli. Kamar a nan an fara da ƙissar Maryam, da dangogin abinci da Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya riƙa samu a wurinta, sai kuma labarinsa na samun haihuwa bayan ya manyanta sosai, ga kuma matarsa bakarara, marar haihuwa, sai labarin haihuwar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba tare da uba ba, sai kuma aka kawo zancen mu'ujizoji daban-daban, kamar raya matattu da Annabi Isa ya riƙa yi da izinin Allah, da sauransu.

3. An kɓe zancen maganar da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mutane a lokacin da yake jariri, da kuma lokacin da ya zama dattijo. Lokacin da yake jariri, wannan abu ne da ya saɓa wa al'adar da aka saba gani, kuma alama ce ta annabcinsa. Lokacin da ya zama dattijo kuwa, ana nufin lokacin da yake kiran mutane zuwa ga bautar Allah da bin shari'arsa.

4. Akwai mayar da martani ga Nasara masu cewa, Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ne, domin da Allah ne da ba zai riƙa canjawa daga yarinta zuwa dattaku ba, domin Allah ba ya caccanzawa.

5. A shari'o'in annabawan da suka gabata ma an samu tsarin shafe wani hukunci a zo da wani sabo, kamar yadda Annabi Isa ya shafe wasu hukunce-hukuncen Attaura.

6. Bayani a kan zamantowar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bawa ne na Allah, ba ɗan Allah ba, kuma ba Allah ne ba.

Suratu Ali-Imran (45-51)

إِذْ قَالَتِ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَٰمَرْيَمُ إِنَّ ٱللَّهَ يُبَشِّرُكِ بِكَلِمَةٍ مِّنْهُ ٱسْمُهُ ٱلْمَسِيحُ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ وَجِيهًا فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِ وَمِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ﴿٤٥﴾ وَيُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِى ٱلْمَهْدِ وَكَهْلًا وَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٤٦﴾ قَالَتْ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِى وَلَدٌ وَلَمْ يَمْسَسْنِى بَشَرٌ ۖ قَالَ كَذَٰلِكِ ٱللَّهُ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ ۚ إِذَا قَضَىٰٓ أَمْرًا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿٤٧﴾ وَيُعَلِّمُهُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ ﴿٤٨﴾ وَرَسُولًا إِلَىٰ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ أَنِّى قَدْ جِئْتُكُم بِـَٔايَةٍ مِّن رَّبِّكُمْ أَنِّىٓ أَخْلُقُ لَكُم مِّنَ ٱلطِّينِ كَهَيْـَٔةِ ٱلطَّيْرِ فَأَنفُخُ فِيهِ فَيَكُونُ طَيْرًۢا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۖ وَأُبْرِئُ ٱلْأَكْمَهَ وَٱلْأَبْرَصَ وَأُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰ بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۖ وَأُنَبِّئُكُم بِمَا تَأْكُلُونَ وَمَا تَدَّخِرُونَ فِى بُيُوتِكُمْ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَةً لَّكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٤٩﴾ وَمُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَىَّ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَلِأُحِلَّ لَكُم بَعْضَ ٱلَّذِى حُرِّمَ عَلَيْكُمْ ۚ وَجِئْتُكُم بِـَٔايَةٍ مِّن رَّبِّكُمْ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿٥٠﴾ إِنَّ ٱللَّهَ رَبِّى وَرَبُّكُمْ فَٱعْبُدُوهُ ۚ هَٰذَا صِرَٰطٌ مُّسْتَقِيمٌ ﴿٥١﴾

45. Ka tuna lokacin da mala'iku suka ce: "Ya ke Maryamu, lalle Allah Yana yi miki albishir da wata kalma daga gare shi, sunansa Almasihu Isa ɗan Maryamu, mai daraja a duniya da lahira, kuma yana cikin bayi makusanta.

46. "Kuma zai riƙa yi wa mutane magana tun yana cikin shimfiɗar jego da kuma lokacin dattijantaka, kuma yana cikin salihan bayi."

47. Sai ta ce: “Ya Ubangijina, ta yaya zan sami ɗa alhalin wani namiji bai kusance ni ba?” Sai ya ce: “Kamar haka ne Allah Yake halittar abin da Ya ga dama. Idan Ya yi nufin wani al’amari, sai Ya ce da shi: “Kasance” Nan take sai ya kasance.

48. “Kuma zai sanar da shi rubutu da hikima da Attaura da Linjila.

49. “Kuma zai aiko shi a matsayin Manzo ga Banu Isra’ila (yana mai cewa): “Lalle ni na zo muku da wata aya daga Ubangijinku; lalle ni zan riƙa mulmula muku taɓo a siffar tsuntsu, sai in yi busa a cikinsa sai ya zama tsuntsu da izinin Allah; kuma zan warkar da wanda aka haifa makaho da mai cutar albaras, kuma in rayar da matattu da izinin Allah; kuma zan riƙa ba ku labarin abin da kuke ci da abin da kuke ajiyewa a gidajenku. Lalle a cikin hakan akwai aya a gare ku in har kun kasance muminai.
50. “Kuma zan zama mai gaskata abin da ya gabace ni na Attaura, kuma don in halatta muku sashin abubuwan da aka haramta muku. Kuma na zo muku da wata aya daga Ubangijinku, don haka ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku yi mini biyayya.

51. “Lalle Allah Shi ne Ubangijina kuma Ubangijinku, don haka ku bautata masa Shi kaɗai. Wannan shi ne tafarki madaidaici.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba wa Annabinsa labarin Maryamu , da haihuwar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Wannan shi ne na uku cikin ƙissoshi huɗu masu tattare da abubuwan mamaki. Allah ya fara da mala’ikun da suka zo ga Maryamu , suna yi mata albishir na za ta haifi yaro, wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai halicce shi da kalmarsa, wato kalmar (كن), ‘kasance’, sai ya kasance, sunansa Almasihu Isa ɗan Maryam. Ana jingina shi ga mahaifiyarsa ne domin ba shi da uba. Yaro wanda daga siffofinsa zai zamo mai daraja ne da matsayi a wurin Allah, duniya da lahira, kuma yana cikin makusantan Allah. Daga cikin mu’ujizojinsa kuma, zai riƙa magana da mutane tun yana jariri cikin zanin haihuwarsa, don ya wanke mahaifiyarsa daga zargin ta haihu ba tare da mijin aure ba, kuma ya yi kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, ba tare da haɗa shi da wani abokin tarayya ba. Bayan ya zama dattijo kuma, zai ci gaba da yi wa mutane magana irin ta annabawan Allah masu karantar da jama’arsu abin da Allah ya yi masa wahayi da shi, sannan yana cikin mutanen kirki.
Sai Maryamu ta amsa da cewa, ta yaya za ta haifi ɗa, alhali ba wani namiji da ya taɓa kusantar ta ta hanyar aure, ko ta hanyar zina? Sai Allah ya mayar mata da amsa cewa, haka dai Allah zai zartar da wannan al’amari da take mamaki, domin da haka Allah yake halittar abin da ya ga damar halitta, kuma babu abin da yake gagarar sa aikatawa, duk sa’adda ya yi nufin samar da wani abu, sai ya ce masa, ‘kasance’, sai nan take abin ya samu, ba tare da ɓata lokaci ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin irin baiwar da ya yi wa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a rayuwarsa ta ilimi da hikimomi iri-iri masu ban al’ajabi. Wannan ƙissa tana bayanin rayuwar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne, musamman bayan girmansa, wadda ita ma take cike da abubuwan ban mamaki, waɗanda har ma suka fi haihuwarsa ba tare da uba ba zama abin mamaki. Allah ya ce, ya yi masa baiwar koya masa rubutu da hikima, wadda ta ƙunshi shari’o’i da siyasar tafiyar da jama’a, ya kuma ba shi ilimin Attaura da Linjila, *sannan ya aiko shi zuwa ga al’ummar Banu Isra’ila*, yana mai faɗa musu cewa: “Lalle na zo muku da wasu hujjoji daga Ubangijinku, waɗanda suke tabbatar da gaskiyar abin da nake faɗa muku cewa ni Manzon Allah ne zuwa gare ku. Hujjojin kuwa su ne, Allah Ya hore mini wasu mu’ujizoji, daga cikin ina iya gina surar mutun-mutumi na tsuntsu da taɓo, sannan in yi busa cikinsa, nan take ya zama tsuntsu mai tashi da izinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma in warkar da mutumin da aka haife shi makaho da mai cutar baras, sannan in tayar da matattu, duk dai da izinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Bugu da ƙari kuma zan iya ba ku labarin irin abincin da kuka ci a gidajenku, da abin da kuke ajiyewa, ba tare da na gani da idona ko wani ya ba ni

labari ba. Duk waɗannan hujjoji ne a gare ku waɗanda suke tabbatar muku gaskiyar abin da na faɗa muku na labarin manzancina gare ku, in har kun kasance masu imani. Sannan kuma ina mai gaskata littafin Attaura da aka saukar a gabanina da kuma Linjila da aka saukar mini. Kuma na zo don in halatta muku wasu abubuwa da aka haramta muku. Na kuma zo muku da wata aya daga Ubangijinku, wadda take nuna gaskiyata, don haka ku kiyaye dokokin Allah, ku bi ni a kan abin da nake kiran ku zuwa gare shi. Lalle Allah shi ne Ubangijina, kuma Ubangijinku, don haka ku bauta masa shi kaɗai; wannan ita ce hanyar Allah miƙaƙƙiya, wadda za ta kai ku ga samun yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).”

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yawan dalilai da ƙarfinsu da yawan mu’ujizoji da bayyanarsu, ba su ne suke sa mutane su karɓi gaskiya ba; sai an samu gamon katari daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Dubi yawan ayoyi da Allah ya gudanar a hannun Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), amma wannan bai hana wasu su ci gaba da kafirce masa ba.

2. Yana daga cikin sunnar annabawa da manzanni, su nemi waɗanda za su tallafa wa da’awarsu.

3. Yana da kyau ga mai da’awa, idan al’amura suka rikice masa, ya nemi taimakon zaɓaɓɓu daga cikin mabiyansa su taimaka masa.

4. Duk wani mai kira zuwa ga wata manufa ko wata aƙida; to dole ne ya kasance yana tare da wasu waɗanda za su riƙa tallafa masa wajen da’awarsa.

5. Duk mai son cin nasara a cikin wani aiki; to dole ne ya yi riƙo da sababin samun wannan nasarar.

6. Cin nasara ba yana nufin sai an fafata faɗa a filin daga ba, a’a, duk wani aikin addini da mutum zai yi da kira zuwa ga addini, shi ma nasara ce.

7. Faɗar Hawariyawa cewa: “Mu ne mataimaka addinin Allah.” yana nufin sun yi watsi da duk wata gargajiya da al’ada tasu marar kyau, sun riƙe addinin Allah shi kaɗai, don haka yanzu a shirye suke su bayar da iya taimakonsu don samun cin nasarar wannan addini.

8. Yana da kyau ko da yaushe a riƙa tuna wa mutane labarin annabawa da manzanni da salihai da suka gabata, domin su san ƙokarinsu, su kuma so su, su yi musu addu’a, kuma su yi koyi da rayuwarsu.

9. A cikin waɗannan ayoyi Allah ya tabbatar da aƙidar ɗauke Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa sama.

10. Musulunci shi ne addinin annabawa da mabiyansu gaba ɗaya.

Suratu Ali-Imran (52-58)

۞فَلَمَّآ أَحَسَّ عِيسَىٰ مِنۡهُمُ ٱلۡكُفۡرَ قَالَ مَنۡ أَنصَارِيٓ إِلَى ٱللَّهِۖ قَالَ ٱلۡحَوَارِيُّونَ نَحۡنُ أَنصَارُ ٱللَّهِ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَٱشۡهَدۡ بِأَنَّا مُسۡلِمُونَ ٥٢ رَبَّنَآ
ءَامَنَّا بِمَآ أَنزَلۡتَ وَٱتَّبَعۡنَا ٱلرَّسُولَ فَٱكۡتُبۡنَا مَعَ ٱلشَّٰهِدِينَ ٥٣ وَمَكَرُواْ وَمَكَرَ ٱللَّهُۖ وَٱللَّهُ خَيۡرُ ٱلۡمَٰكِرِينَ ٥٤ إِذۡ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَىٰٓ إِنِّي مُتَوَفِّيكَ
وَرَافِعُكَ إِلَيَّ وَمُطَهِّرُكَ مِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَجَاعِلُ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوكَ فَوۡقَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِۖ ثُمَّ إِلَيَّ مَرۡجِعُكُمۡ فَأَحۡكُمُ بَيۡنَكُمۡ

فِيمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ ٥٥ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَأُعَذِّبُهُمۡ عَذَابٗا شَدِيدٗا فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٥٦ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَيُوَفِّيهِمۡ أُجُورَهُمۡۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥٧ ذَٰلِكَ نَتۡلُوهُ عَلَيۡكَ مِنَ ٱلۡأٓيَٰتِ وَٱلذِّكۡرِ ٱلۡحَكِيمِ ٥٨

52. To yayin da Isa ya ga alamun kafirci a tare da su sai ya ce: “Su wane ne za su taimake ni wajen kira zuwa ga Allah?” Sai Hawariyawa suka ce: “Mu ne mataimaka addinin Allah, mun yi imani da Allah, kuma ka ba da shaida cewa, mu Musulmai ne.

53. “Ya Ubangijinmu, mun yi imani da abin da Ka saukar, kuma mun yi ɗa’a ga Manzo, don haka Ka rubuta mu tare da masu shaida.”

54. Sai suka shirya makirci, sai Allah Ya mayar musu da martani game da makircinsu; kuma Allah Shi ne Fiyayyen masu mayar da martanin makirci.
55. Kuma ka tuna lokacin da Allah Ya ce: “Ya kai Isa, lalle Ni Mai karɓar ranka ne, kuma Ni Mai ɗaukaka ka ne zuwa gare Ni, kuma zan tsarkake ka daga (cutarwar) waɗanda suka kafirta, kuma zan ɗora waɗanda suka bi ka a kan waɗanda suka kafirce maka har zuwa ranar tashin alƙiyama; sannan zuwa gare Ni ne makomarku take, sai In yi hukunci a tsakaninku game da abin da kuke saɓani a kansa.

56. Amma waɗanda suka kafirce, zan yi musu azaba mai tsanani a duniya da lahira, kuma ba su da wasu mataimaka.”

57. Amma kuma waɗanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyuka nagari, to (Allah) zai cika musu ladansu. Kuma Allah ba Ya son azzalumai.

58. “Wannan (labara) Muna karanta maka shi ne daga ayoyi da kuma Alkur’ani mai hikima.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba mu labarin cewa, lokacin da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ga alamar bijirewa da kafircewa daga Banu Isra’ila da ƙaryata annabcinsa, sai ya nemi taimako daga zaɓaɓɓu cikin almajiransa, yana mai kiran su da cewa, wane ne zai taimaka masa a kan wannan kira da yake yi zuwa ga addinin Allah? Sai suka amsa da cewa, su za su zama masu taimakon addinin Allah, sannan suka shelanta imaninsu a fili, kuma suka kafa shi shaida a kan Musuluncinsu, suka kuma roƙi Ubangijinsu, suna masu kamun ƙafa da imaninsu da littafin Linjila da ya saukar ga Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kuma biyayyarsu gare shi da cewa, Allah ya rubuta su cikin waɗanda suka ba da gaskiya da Kaɗaitakar Allah da gaskiyar manzannin Allah, kuma suka bi umarninsa, suka kauce wa abin da ya hana.

An karɓo daga Abdullah ɗan Mas'ud (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani annabi gabanina da Allah ya aiko shi cikin wata al'ummarsa sai ya kasance a cikin al'ummar tasa yana da hawariyawa da sahabbai waɗanda suke riƙo da sunnarsa suke kuma koyi da umarninsa..." [Muslim #50].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma sai ya ba da labarin irin makircin da Banu Isra’ila suka ƙulla ga Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), na ƙoƙarin hallaka shi. Su suna ƙulla makircinsu, Allah kuma yana shirya musu martani a kan makircinsu, domin Allah shi ne mafi iya mayar da martanin makirci, kuma mafi ƙarfi, mafi sani. Don haka sai Allah ya jefa kamannin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a kan ɗaya daga cikinsu, sai suka kama shi suka kashe shi, suna zaton Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne suka kashe. Shi kuma Allah ya jefa masa barci, sannan ya ɗauke shi zuwa sama.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa game da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, zai karɓi ransa irin karɓar ran mai barci, sannan zai ɗaukaka shi zuwa gare shi da gangar jikinsa da kuma ruhinsa, sannan zai kuɓutar da shi daga waɗanda suka kafirta, ya fitar da shi, ya ɗaga shi zuwa sama, sannan zai sanya mabiyansa su zama su ne masu rinjaye a kan kafirai da ƙarfin hujja da izza da ɗaukaka har zuwa tashin alƙiyama. Waɗannan mabiyan nasa da Allah yake yi wa wannan alƙawari, su ne Nasara, waɗanda suka tsaya daidai a kan koyarwarsa har zuwa lokacin aiko Annabi Muhammad (ﷺ), sai kuma Musulmi waɗanda su ne mabiya na gaskiya ga Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), waɗanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafe su, ya ba su nasara a kan Yahudawa da Nasara da sauran kafirai.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa masu saɓani cikin lamarin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, dukkansu makomarsu zuwa gare shi take, kuma zai yi hukunci a tsakaninsu game da wannan saɓani da suke yi. Hukuncinsa kuwa shi ne, zai yi musu azaba mai tsanani a nan duniya, ta hanyar kisa da ɗauri da ƙaskanci da wulaƙanci da raba su da dukiyoyinsu da ƙuncin zukata da za su yi ta fama da shi, sannan kuma a lahira su gamu da azabar Jahannama, a lokacin da babu wanda zai taimaka musu, ya kare su daga azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Su kuma waɗanda suka yi imani, kuma suka yi aiki na ƙwarai, hukuncinsa a kansu shi ne, zai cika musu ladansu babu ragi ko tawaya a duniya da lahira. A nan duniya ta hanyar ba su nasara kan abokan gabarsu, da izza da rayuwa mai kyau da kyakkyawan ambato da sauransu, a lahira kuwa ya saka musu da gidan Aljanna cikin ni'ima ta har abada. Kuma Allah ba ya son azzalumai, don haka shi kansa babu yadda za a yi ya yi zalunci cikin hukuncinsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce da Annabinsa waɗannan labarai da yake ba shi na Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifiyarsa Maryamu da sauran ƙissoshi da aka ambata an karanta masa su ne don su zama hujjoji masu nuna gaskiyarsa da gaskiyar annabinsa, sannan kuma suna daga cikin ƙissoshin Alƙur'ani ne, mai cike da hikimomi, kuma mai yanke hukunci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin yin *mubahala*, wato addu'ar tsinuwa tsakanin mai kira zuwa ga gaskiya da masu faɗa da ita, da sharaɗin ya kasance yana da yaƙini a kan abin da zai yi *mubahalar* a kansa, kuma muhimmin abu ne mai girma, sannan ya zamana ya isar da hujjojinsa ga abokin husuma ya fahimce shi amma ya yi girman kai.

2. Duk wanda zai juya wa addinin Allah baya; to wannan mutum mabarnaci ne, ko da kuwa ya kirawo kansa mai gyara.

3. Halaccin yin la'ana ga duk wanda ya saɓa wa gaskiya, amma ta fuskar aikinsa, ba ta ambaton sunan wani ba.

Suratu Ali-Imran (59-63)

إِنَّ مَثَلَ عِيسَىٰ عِندَ ٱللَّهِ كَمَثَلِ ءَادَمَ ۖ خَلَقَهُۥ مِن تُرَابٍ ثُمَّ قَالَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿٥٩﴾ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُن مِّنَ ٱلْمُمْتَرِينَ ﴿٦٠﴾ فَمَنْ حَآجَّكَ فِيهِ مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلْعِلْمِ فَقُلْ تَعَالَوْا۟ نَدْعُ أَبْنَآءَنَا وَأَبْنَآءَكُمْ وَنِسَآءَنَا وَنِسَآءَكُمْ وَأَنفُسَنَا وَأَنفُسَكُمْ ثُمَّ نَبْتَهِلْ فَنَجْعَل لَّعْنَتَ ٱللَّهِ عَلَى ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿٦١﴾ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ ٱلْقَصَصُ ٱلْحَقُّ ۚ وَمَا مِنْ إِلَٰهٍ إِلَّا ٱللَّهُ ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٦٢﴾ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٦٣﴾

59. Lalle misalin Isa a wurin Allah kamar misalin Adamu ne; Ya halicce shi daga turɓaya, sannan Ya ce da shi: "Kasance." nan take sai ya kasance.

60. Gaskiya ce daga wajen Ubangijinka, don haka kar ka kasance cikin masu yin kokwanto.

61. To duk wanda ya yi jayayya da kai cikin lamarinsa (Isa) bayan abin da ya zo maka na ilimi, to ka ce: “Ku zo mu kirawo ‘ya’yanmu da ‘ya’yanku da matanmu da matanku da mu kanmu da ku kanku, sannan mu ƙaƙantar da kawunanmu cikin addu’a don mu roƙi tsinuwar Allah ta tabbata a kan maƙaryata”.

62. Lalle wannan shi ne ba da labari na gaskiya. Kuma babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah. Kuma lalle Allah Shi ne Mabuwayi, Mai hikima.

63. To idan sun ba da baya, to lalle Allah Yana sane da maɓarnata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tsayar da hujja a kan Nasara waɗanda suke bautar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da sunan shi Allah ne, ko kuma ɗan Allah ne, saboda an same shi ba uba. Allah yana kwatanta musu cewa, samar da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba uba da samar da Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba uwa ba uba, Allah ya halicce shi kawai da ƙasa, ya ce masa, ‘kasance’, sai ya kasance kamar yadda Allah ya yi nufinsa duka abu ɗaya ne a wurin Allah. To idan har suna ganin samuwar Annabi Isa ba uba dalili ne da zai sa su riƙe shi Allah, ko ɗan Allah; to me ya sa ba su yi haka ga Annabi Adamu ba, alhali ga shi samuwarsa ta fi ta Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ban al’ajabi?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shaida wa Annabinsa cewa, wannan labarin da ya ba shi na Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) gaskiya ce daga Ubangijinsa, don haka kada ya zama cikin masu shakka. Hasali ma idan har wani ya zo yana jayayya da shi cikin lamarin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), bayan abin da ya zo masa na ilimi da gamsasshen bayani a kan wannan batu; to ya faɗa wa masu jayayya da shi cewa, shi da su gaba ɗaya, su fito da ‘ya’yansu, da matansu, da su kansu, sai a taru a yi addu’a, Allah ya la’anci maƙaryaci a tsakaninsu. Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas yana cewa: “Lokacin da wannan ayar ta sauka, Manzon Allah (ﷺ) ya kirawo Aliyyu da Faɗimatu da Hasan da Husaini, ya ce: “Ya Allah, waɗannan iyalaina ne.” [Muslim #2404].

An karɓo daga Huzaifa ya ce: “Wasu mutane su biyu daga mutanen Najarana ɗaya ana ce masa Al-Aƙibu, ɗayan kuwa Assayyidu, sun zo ga Annabi (ﷺ) suna so su yi tsinuwa tsakaninsa da su (game da sha’anin Annabi Isa), sai ɗayansu ya ce wa ɗan’uwansa: ‘Kada ka yi wannan aikin, Wallahi idan ya zamanto Annabi ne da gaske, sannan muka yi tsinuwa tsakaninmu da shi; to da mu da zurriyyarmu ba za mu rabauta ba har abada.’ Daga nan sai suka fasa, suka nemi sulhu da Annabi (ﷺ) a kan za su ba shi duk abin da ya nema daga gare su na dukiyar sulhu.” [Dubi, Bukhari #4350, da Muslim #2420].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara jaddada wa Annabinsa (ﷺ) cewa, wannan labari da yake ba shi na Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne labarin gaskiya, duk wani labari da ya ci karo da shi, to ba gaskiya ba ne, ƙarya ne. Kuma babu wani wanda ya cancanci a bauta masa sai Allah shi kaɗai, Mabuwayi da ya gagari kowa da komai, Mai hikima cikin duk ayyukansa.
To idan waɗannan sun bijire wa gaskiya, sun riƙi ƙarya; to sun tabbata maɓarnata, Allah kuwa yana sane da su, kuma zai yi musu sakayya a kan ayyukansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubawa kamar haka:

1. Ya kamata Musulmi ya riƙa alfahari da cewa, shi Musulmi ne a ko’ina, kuma a gaban kowane ne. Ba kamar yadda wasu raunanan Musulmi suke jin kunyar su ce su Musulmai ne a gaban waɗanda ba Musulmai ba.

2. Adalci yayin tattaunawa da wanda ba Musulmi ba dole ne, balle kuma tare da wanda yake Musulmi ne.

3. Amfanin karantar tarihi, domin zai taimaka wajen rushe ƙarairayi da dama waɗanda suka saba wa abin da ya tabbata a tarihi.

4. Kafa hujja da hankali a kan gaskiya, kuma duk wani lafiyayyen hankali idan mai shi ya yi amfani da shi; to zai kai shi ga fahintar gaskiya. Sai dai ba daidai ba ne mutum ya dogara a kan hankalinsa gaba ɗaya, ya watsar da nassi.

5. Imani shi ne musabbabin jiɓinta ta Ubangiji ga bawansa.

Suratu Ali-Imran (64-68)

قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ تَعَالَوْا۟ إِلَىٰ كَلِمَةٍ سَوَآءٍۭ بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمْ أَلَّا نَعْبُدَ إِلَّا ٱللَّهَ وَلَا نُشْرِكَ بِهِۦ شَيْـًٔا وَلَا يَتَّخِذَ بَعْضُنَا بَعْضًا أَرْبَابًا مِّن دُونِ ٱللَّهِ ۚ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَقُولُوا۟ ٱشْهَدُوا۟ بِأَنَّا مُسْلِمُونَ ﴿٦٤﴾ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ لِمَ تُحَآجُّونَ فِىٓ إِبْرَٰهِيمَ وَمَآ أُنزِلَتِ ٱلتَّوْرَىٰةُ وَٱلْإِنجِيلُ إِلَّا مِنۢ بَعْدِهِۦٓ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿٦٥﴾ هَٰٓأَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ حَٰجَجْتُمْ فِيمَا لَكُم بِهِۦ عِلْمٌ فَلِمَ تُحَآجُّونَ فِيمَا لَيْسَ لَكُم بِهِۦ عِلْمٌ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴿٦٦﴾ مَا كَانَ إِبْرَٰهِيمُ يَهُودِيًّا وَلَا نَصْرَانِيًّا وَلَٰكِن كَانَ حَنِيفًا مُّسْلِمًا وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٦٧﴾ إِنَّ أَوْلَى ٱلنَّاسِ بِإِبْرَٰهِيمَ لَلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ وَهَٰذَا ٱلنَّبِىُّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ۗ وَٱللَّهُ وَلِىُّ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٦٨﴾

64. Ka ce: “Ya ku Ma’abota Littafi, ku taho ga wata kalma mai daidaitawa tsakaninmu da ku cewa, kar mu bauta wa kowa sai Allah, kuma kar mu haɗa Shi da wani, kuma kada wani sashi a cikinmu ya riƙi wani sashi a matsayin abin bauta ba Allah ba.” Idan kuwa sun ba da baya, to ku ce: “Ku shaida cewa, lalle mu Musulmi ne.”

65. Ya ku Ma’abota Littafi, don me kuke yin jayayya game da Ibrahimu, alhalin ba a saukar da Attaura da Linjila ba sai bayan shuɗewarsa? Yanzu ba za ku hankalta ba?

66. Ga ku nan ku waɗannan kun yi jayayya kan abin da kuke da ilimi a kai, to don me kuma kuke jayayya a kan abin da ba ku da ilimi a kansa? Kuma Allah Yana sane ku ba ku sani ba.

67. Ibrahimu bai taɓa zama Bayahude ba, sannan bai taɓa zama Banasare ba, sai dai ya kasance mai barin ɓarna ne, Musulmi, kuma bai kasance ɗaya daga cikin mushirikai ba.

68. Lalle mafi kusancin mutane da Ibrahimu su ne waɗanda suka bi shi, sai kuma wannan Annabin, da kuma waɗanda suka yi Imani. Kuma Allah shi ne Majiɓincin al’amuran muminai.

Bayan an kira Ma’abota Littafi zuwa ga addu’ar tsinuwa amma sun ƙi yarda, sannan an kawo musu hujjoji iri-iri waɗanda suka nuna ɓacin addinin da suke kai, sun kuma kasa kare ɓatansu, kuma Allah ya riga ya san yadda Annabi (ﷺ) yake matuƙar tausayin su, yana kwaɗayin shiriyarsu, sai Allah ya umarce shi da ya kirawo su gaba ɗaya zuwa ga kalma ta bai-ɗaya, wadda kowa da kowa zai daidaita a kanta, kuma za su haɗa kai a kanta. Wannan kalma ita ce kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da bauta, watau kada a bauta wa wani ba shi ba, mala’ika ne, ko wani annabi, ko waliyyi, ko wani gunki. Kada kuma su ɗauki wasu iyayen giji, suna bauta musu ba Allah ba, har su riƙa halatta musu haram ko su haramta

musu halal su kuma yarda. To idan sun bijire, sun ƙi yarda da wannan kiran; to ku muminai ku kafa su shaida cewa, ku Musulmi ne, kuma za ku ci gaba da bin wannan addinin da Allah ya zaɓa muku.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fuskantar da maganarsa ga Yahudawa da Nasara cewa, don mene ne suke jayayya game da lamarin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi); kowanne yana da'awar cewa a kan addininsa yake, Yahudawa suna cewa shi Bayahude ne, Nasara ma suna cewa shi Banasare ne, alhalin yadda gaskiyar al'amarin take, littafin Attaura da littafin Linjila, ba a saukar da su ba sai bayan mutuwarsa da lokaci mai tsawo. Yanzu ba za su yi aiki da hankulansu ba, su gane cewa, abin da suke faɗa ƙarya ne? To ga shi yanzu su Yahudu da Nasara suna jayayya a kan abin da suke da ilimi a kansa na al'amarin addininsu, da abin da aka ambata a littattafansu. To amma me ya sa za su rika jayayya a kan abin da ba su da ilimi a kansa na lamarin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da addinin da ya rayu a kansa? Allah kam iliminsa ya kewaye komai, ya san abin da su ba su sani ba, amma su ba su san komai ba daga abin da Allah ya sani.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana musu gaskiyar al'amarin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ƙaryata maganar cewa shi Bayahude ne, ko Banasare. Allah ya tabbatar da cewa, Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) tsaye yake ƙyam a kan addinin gaskiya, ba ruwansa da duk wata ɓarna da shirka, yana bin umarnin Allah cikin ikhlasi, kuma ba ya cikin masu haɗa Allah da wani, masu bautar gumaka.Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci waɗanda suka fi cancantar su zama tare da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya bayyana cewa, su ne waɗanda suka bi addininsa, suka kuma bi hanyarsa ta kaɗaita Allah a wajen bauta, waɗanda su ne Annabi (ﷺ), da sahabbansa, da muminai da za su zo bayansu. To waɗannan su suka fi cancanta su zama masoyansa, majiɓintansa, kuma Allah shi ne yake jiɓintar lamarin muminai, ya taimaka musu, ya ba su nasara a kan abokan gabarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk azzalumi akan saka masa da irin zaluncinsa, ko a jarrabe shi da irin cutar da yake ƙoƙarin ya yi wa wasu.

2. Mutum yakan makance ya kasa ganin ɓatan da yake ciki.

3. Wajibi ne a yi taka-tsantsan da maɓarnata yayin da suka gauraya ƙarya da gaskiya, kuma kada a ruɗu da daɗin bakinsu.

4. Kakkausar suka ga duk mai cakuɗa ƙarya da gaskiya, kuma yake ɓoye gaskiya. Domin ambaton Ma'abota Littafi a nan, ba don ana nufin sai su kaɗai ba; duk wanda ya yi irin wannan aiki ya shiga cikin wannan sukar.

5. Taƙarƙarewar da Yahudu da Nasara suka yi wajen ganin sun ɓatar da Musulmi shi ya hana su su bi gaskiya, domin duk sa'adda mutum ya dage kan wani mugun abu; to sai ya manta da abin da wannan abin kan iya haifar masa nan gaba.

6. Mai ɓoye gaskiya ba shi da wata hanyar yin hakan sai ta fuskoki biyu:
Fuska ta Farko: Ya jeho wani abu mai rikitarwa don ya tabbatar da ƙarya.
Fuska ta Biyu: Ya ɓoye duk wani dalili da zai fito da gaskiya.

7. Haɗa ƙarya da gaskiya shi ne sanadiyyar ɓacewar al'ummomin da suka gabace mu, kuma shi ne mafarar duk wata bidi'a, domin ita bidi'a, da a ce ƙarya ce tsantsarta; to ba za ta samu karɓuwa ba, da

kowa ya yi watsi da ita; da kuma a ce gaskiya ce tsantsa, to da ba ta zama bidi'a ba, da ta zama daidai da Sunna. Sai dai an gauraya ƙarya ce da gaskiya wuri guda, sai wasu su kasa gane ƙaryar da ke cikinta.

Suratu Ali-Imran (69-71)

وَدَّت طَّآئِفَةٌ مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ لَوۡ يُضِلُّونَكُمۡ وَمَا يُضِلُّونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمۡ وَمَا يَشۡعُرُونَ ٦٩ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لِمَ تَكۡفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَأَنتُمۡ تَشۡهَدُونَ ٧٠ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لِمَ تَلۡبِسُونَ ٱلۡحَقَّ بِٱلۡبَٰطِلِ وَتَكۡتُمُونَ ٱلۡحَقَّ وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٧١

69. Wata ƙungiya daga cikin Ma'abota Littatafi sun yi burin ina ma sun ɓatar da ku, kuma ba za su ɓatar da kowa ba sai kawunansu, amma ba sa sanin hakan.

70. Ya ku Ma'abota Littafi, don me kuke kafirce wa ayoyin Allah, alhalin ku kuna shaidawa (cewa gaskiya ne)?
71.Ya ku Ma'abota Littafi, don me kuke cakuɗa gaskiya da ƙarya, kuma kuke ɓoye gaskiya, alhalin ku kuna sane?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a nan yana gargaɗin bayinsa muminai ne game da makircin wata ƙungiya ta Yahudawa da Nasara, waɗanda ba su da wani buri a rayuwarsu, sai na ganin Musulmai sun lalace sun ɓace, sun yi watsi da addininsu na Musulunci, ba don komai ba sai don hassada da suke nuna musu. Sai dai makircinsu su kaɗai zai ci, domin kansu kawai suke ƙara ɓatarwa, don haka duk ƙoƙarin da suke yi na ɓatar da Musulmi yana komawa ne a kansu, suna ƙara dulmiya ne cikin ɓata da taɓewa, amma su ba su san hakan ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya soki abin da Ma'abota Littafi suke aikatawa, yana cewa, don me suke kafirce wa Alƙur'ani, alhalin sun san gaskiya ne, suna kuma shaidawa a kan hakan, domin sun karanta siffofin Annabi (ﷺ) a littattafansu? Kuma don me suke cakuɗa ƙarya da gaskiya, har a kasa bambancewa tsakaninsu, kuma su ɓoye gaskiya alhalin suna sane da ɓarnar da suke yi?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗin Musulmin da ake amfani da su don jefa shakka a cikin zukatan raunanansu, ta hanyar yi wa Musulunci tuhumce-tuhumce iri-iri don a ɓata shi a idon 'ya'yansa, a ɓata tarihinsa da koyarwarsa da nassoshinsa. Ta hanyar sunaye waɗannan raunanan mutane suke nuna su Musulmi ne, amma suna taka rawa a gefe guda irin ta Yahudawa.

2. Wanda duk ya nemi shiriya ba ta hanyar Alƙur'ani da sunna ba; to ya ɓace, domin babu shiriya sai wadda Manzon Allah (ﷺ) ya zo da ita.

3. Amfanin ba da labarin wannan makirci na Yahudawa na cewa su yi imani da farkon yini, daga ƙarshensa sai su yi ridda. Amfanin fallasa su shi ne:
• **Na Ɗaya:** Wannan shirin nasu sun yi shi ne a ɓoye, ba wani Musulmi da ya san da shi; to yayin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo yana ba da labarin wannan sirri nasu, hakan ya nuna cewa lalle shi Manzon Allah ne, domin ya ba da labarin wani abu da ba wanda ya san shi sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya sanar da shi.
• **Na Biyu:** Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fallasa wannan mugun shiri nasu; sai ya zama ba zai yi wani tasiri ba a zukatan muminai, don ba don haka ba, da wataƙila a ga tasirinsa a wurin wasu masu raunin imani.

• **Na Uku:** Za su ji tsoron ƙara ƙulla wani makircin irin wannan bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tona asirinsu.

Suratu Ali-Imran (72-74)

وَقَالَت طَّآئِفَةٌ مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ ءَامِنُواْ بِٱلَّذِيٓ أُنزِلَ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَجۡهَ ٱلنَّهَارِ وَٱكۡفُرُوٓاْ ءَاخِرَهُۥ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٧٢ وَلَا تُؤۡمِنُوٓاْ إِلَّا لِمَن تَبِعَ دِينَكُمۡ قُلۡ إِنَّ ٱلۡهُدَىٰ هُدَى ٱللَّهِ أَن يُؤۡتَىٰٓ أَحَدٞ مِّثۡلَ مَآ أُوتِيتُمۡ أَوۡ يُحَآجُّوكُمۡ عِندَ رَبِّكُمۡۗ قُلۡ إِنَّ ٱلۡفَضۡلَ بِيَدِ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ ٧٣ يَخۡتَصُّ بِرَحۡمَتِهِۦ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٧٤

72. Kuma wata ƙungiya cikin Ma’abota Littafi suka ce: “Ku yi imani mana da abin da aka saukar wa waɗanda suka yi imani a farkon yini, kuma ku kafirce a ƙarshen yini, mai yiwuwa ne su dawo (daga rakiyar addininsu).

73. “Kuma kada ku amince da kowa sai wanda ya bi addininku.” Ka ce: “Lalle shiriya ita ce shiriyar Allah, domin kar (ku yarda a ce) an ba wani mutum irin abin da aka ba ku, ko kuma ku ba su dama su yi jayayya da ku a wajen Ubangijinku.” Ka ce: “Lalle falala a hannun Allah take, Yana bayar da ita ga wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mai yalwa ne, Mai yawan sani.

74. “Yana keɓantar wanda Ya ga dama da rahamarsa, kuma Allah Ma’abocin falala ne wadda take mai girma.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin wasu miyagun mutane ne a cikin Yahudawa da Nasara, waɗanda suke ta ƙulle-ƙullen makirci ga Musulmi ta hanyar kawo ruɗu na addini ga wasu raunanan Musulmi. Sun yanke shawara a tsakaninsu cewa, su bayyana imaninsu da abin da Manzon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zo da shi a farkon yini; idan yamma ta yi kuma su kafirce masa. Yin haka shi zai sa masu raunin fahinta cikin muminai su riƙa cewa, da a ce wannan addinin gaskiya ne, da waɗanda suka yi imani da shi cikin Ma’abota Littafi, ba su yi ridda ba. Manufarsu ita ce Musulmi su watsar da addininsu gaba ɗaya.
Sannan magana ta dawo kan tattaunawar Yahudawa a tsakaninsu, da irin yadda suke yi wa junansu wasiyya, yayin da wasunsu suka faɗa wa wasu cewa, kada su yarda da kowa idan ba wanda yake bin addininsu ba, kada kuma su yarda su bayyana sirrinsu ga wani Musulmi don kada ya samu irin ilimin abin da suka samu; idan har sun yi haka to za su koye shi, su ma sai su zama masu ilimi ko kuma su riƙe shi a matsayin abin da za su kafa musu hujja da shi a gaban Allah, sai su ba da shaidar cewa, gaskiya ta bayyana gare su, ƙin bi suka yi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce wa Annabinsa ya faɗa musu cewa, shiriya a hannun Allah take, yana bayar da ita ga wanda ya ga dama daga bayinsa. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai yalwar falala ne, mai yawan kyauta, kuma mai cikakken sani ne game da waɗanda suka cancanci a kyautata musu, don haka yana yin kyautarsa ne ga wanda ya cancanta, ya kuma hana wanda bai cancanta ba kuma yana keɓance wanda ya ga dama da rahamarsa, kuma shi ma’abocin falala ne mai yawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A cikin Ma’abota Littafi da mushirikai za a iya samun masu amana, don haka ana iya ba wa ɗayansu amanar dukiya. Ya halatta Musulmi ya ɗauki kafiri mai amana aikin likitanci, domin wannan yana daga cikin karɓar labarin abin da suka sani na sha’anin duniya. Wannan ya halatta, sai dai idan an hango wata ɓarna; to sai a kauce mata. Duk da halaccin yin haka amma mu’amala da Musulmi mai amana ta fi.

2. Wanda duk ya yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ƙarya yana sane, ya fi girman zunubi, fiye da wanda ya yi masa ƙarya bisa ga rashin sani.

3. Wanda duk ya cika alƙawarin da ya ɗaukar wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya guji ƙarya ko yaudara; to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai so shi, ya yi masa rahama duniya da lahira.

4. Cika alƙawarin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙunshi alƙawarin da ke tsakaninsa da bawansa na bauta masa, da ba shi haƙƙoƙinsa, da kuma alƙawarin da ke tsakanin bawa da sauran 'yan'uwansa bayi.

5. Tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da bawa zai siffanta da shi, shi ne zai sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya so shi.

6. Duk wata mu'amala mai kyau da bawa zai yi; to ya yi domin neman yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), da haka ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai saka masa da soyayyarsa gare shi.
Suratu Ali-Imran (75-76)

*وَمِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ مَنۡ إِن تَأۡمَنۡهُ بِقِنطَارٖ يُؤَدِّهِۦٓ إِلَيۡكَ وَمِنۡهُم مَّنۡ إِن تَأۡمَنۡهُ بِدِينَارٖ لَّا يُؤَدِّهِۦٓ إِلَيۡكَ إِلَّا مَا دُمۡتَ عَلَيۡهِ قَآئِمٗاۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَالُواْ لَيۡسَ عَلَيۡنَا فِي ٱلۡأُمِّيِّـۧنَ سَبِيلٞ وَيَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ٧٥ بَلَىٰ مَنۡ أَوۡفَىٰ بِعَهۡدِهِۦ وَٱتَّقَىٰ فَإِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَّقِينَ ٧٦

75. Kuma daga cikin Ma'abota Littafi akwai wanda in da za ka ba shi amana ta dukiya mai yawa, zai dawo maka da ita, daga cikinsu kuwa akwai wanda idan da za ka ba shi amana ta dinare ɗaya, ba zai dawo maka da shi ba, sai fa idan ka tashi tsaye a kansa. Wannan kuwa saboda sun ce: "Babu wani laifi a kanmu (don mun ci dukiyar) bobayin mutane." Kuma suna faɗin ƙarya su jingina wa Allah, alhalin su suna sane.

76. Ba haka ba ne, duk wanda ya cika alƙawarinsa, kuma ya tsare dokar Allah, to lalle Allah Yana son masu taƙawa.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana irin ƙaryar da Yahudawa suke yi na cewa an ba su matsayi na ilimi da addini wanda ba wanda aka ba irinsa, da kuma nuna cewa bin addininsu kaɗai shi ne shiriya, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a nan ya ƙaryata su, ya nuna su a matsayin maciya amana, waɗanda mu'amalarsu da mutane babu gaskiya a cikinta, kamar yadda mu'amalarsu da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ita ma babu gaskiya a cikinta ko kaɗan.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a cikin ma'abota Littafi akwai mai amana, wanda idan da za ka ba shi amanar dukiya komai yawanta, ba zai ci komai daga cikinta ba, zai dawo maka da ita kamar yadda ka ba shi. Daga cikinsu kuma akwai maci amana wanda da za ka ba shi ɗan kuɗi kaɗan, kamar Dinari ɗaya; to ba zai taɓa dawo maka da kayanka ba, sai ka yi tsayuwar daka a kansa, ka matsa masa, sannan zai dawo da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin wannan mugun hali nasu da cewa, saboda suna riyawa ne cewa, ba su da wani laifi don sun ci dukiyar waɗanda ba Yahudawa ba, wato suna nufin Musulmi. Watau a nan sun haɗa laifuka biyu: Laifin cin dukiyar haram da kuma laifin halatta haram. To wannan ita ce ƙaryar da suka yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), alhalin sun san ƙarya suke.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rushe wannan da'awar tasu, da cewa, al'amarin ba haka yake ba. Duk wani Bayahude ko Banasare idan ya cika alƙawarin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi da su, ya yi imani da Annabi (ﷺ) da Alƙur'anin da ya saukar masa, ya kiyaye dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta hanyar aikata abin da aka umarce shi da barin abin da aka hana shi; to lalle ya sani Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son masu taƙawa cikin bayinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda ya tilasta wa mutane su bi maganarsa, su yi masa ɗa'a a kowanne hali; to ya zama mai kiran su su bauta masa, ba Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba.

2. Ya kamata mutum ya zama mai koyar da ilimi, kuma malami na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), domin duk malamin da ba na Allah ba; to iliminsa na banza ne ba zai amfane shi da komai ba.

3. Bayanin kafircin waɗanda suke bauta wa mala'iku ko annabawa ko waliyyai ko kuma malamai.

4. Karya alƙawari da yarjejeniya yana daga cikin manya-manyan abubuwan da suke kawo matsala a zamantakewar al'umma, shi ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin narko mai tsanani ga waɗanda suke karya alƙawali.

5. Malami ba shi ne wanda ya cika ƙwaƙwalen mutane da ilimi ba kawai, a'a dole sai ya haɗa da yi musu tarbiyya ta ƙwarai.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da masu sayen wani abin duniya da alƙawarin da ke tsakaninsu da Allah. Malamai masu ɓoye gaskiya don wani abin duniya sun shiga cikin wannan gargaɗi.

7. Hukuncin alƙali ba ya halatta haram. Don haka ko alƙali ya yi hukuncin danƙa dukiyar wani ga wanda ba tasa ba, saboda abin da ya bayyana gare shi na dalilai, to wannan ba ya halatta masa wannan abin.

Suratu Ali-Imran (77-80)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يَشۡتَرُونَ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ وَأَيۡمَٰنِهِمۡ ثَمَنٗا قَلِيلًا أُوْلَٰٓئِكَ لَا خَلَٰقَ لَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ وَلَا يُكَلِّمُهُمُ ٱللَّهُ وَلَا يَنظُرُ إِلَيۡهِمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَلَا يُزَكِّيهِمۡ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٧٧ وَإِنَّ مِنۡهُمۡ لَفَرِيقٗا يَلۡوُۥنَ أَلۡسِنَتَهُم بِٱلۡكِتَٰبِ لِتَحۡسَبُوهُ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَمَا هُوَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَيَقُولُونَ هُوَ مِنۡ عِندِ ٱللَّهِ وَمَا هُوَ مِنۡ عِندِ ٱللَّهِ وَيَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ٧٨ مَا كَانَ لِبَشَرٍ أَن يُؤۡتِيَهُ ٱللَّهُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحُكۡمَ وَٱلنُّبُوَّةَ ثُمَّ يَقُولَ لِلنَّاسِ كُونُواْ عِبَادٗا لِّي مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِن كُونُواْ رَبَّٰنِيِّـۧنَ بِمَا كُنتُمۡ تُعَلِّمُونَ ٱلۡكِتَٰبَ وَبِمَا كُنتُمۡ تَدۡرُسُونَ ٧٩ وَلَا يَأۡمُرَكُمۡ أَن تَتَّخِذُواْ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ أَرۡبَابًاۚ أَيَأۡمُرُكُم بِٱلۡكُفۡرِ بَعۡدَ إِذۡ أَنتُم مُّسۡلِمُونَ ٨٠

77. Lalle waɗanda suke musanya alƙawarin Allah da rantse-rantsensu da wani ɗan farashi ƙanƙani, waɗannan ba su da wani rabo a lahira, kuma Allah ba zai yi musu magana ba, kuma ba zai dube su (duba na rahama) ba a ranar alƙiyama, kuma ba zai tsarkake su ba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi.

78. Kuma lalle daga cikinsu akwai wani ɓangare da suke karkatar da harshensu lokacin karanta Littafin (Attaura), don ku yi zaton yana cikin Littafin, alhali kuwa ba ya cikin Littafin, kuma za su riƙa cewa, shi (wahayi ne saukakke) daga wurin Allah, alhalin kuwa ba daga wurin Allah yake ba, kuma za su riƙa faɗar ƙarya suna jingina wa Allah, alhalin suna sane.

79. Bai dace ba ga wani mutum wanda Allah zai ba shi littafi da hukunci da annabci, sannan ya ce wa mutane: "Ku zama bayina ba na Allah ba," sai dai (ya ce): "Ku zamo malamai na Allah saboda abin da kuke karantarwa na littafi, kuma saboda abin da kuka kasance kuna karantawa."

80. Kuma ba zai umarce ku da ku riƙi mala'iku ko annabawa a matsayin iyayengiji ba; yanzu zai umarce ku da kafirci ne bayan kuna Musulmi?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin irin uƙubar da ya tanadar wa waɗanda suke karya alƙawarin da suka yi tsakaninsu da shi, su canja shi don wani abu na duniya da bai taka kara ya karya ba, maimakon su yi biyayya ga Annabi (ﷺ), su yi imani da shi, sai su riƙa rantsuwar ƙarya don su samu wani abin duniya. Allah ya ce, waɗannan ne ba su da wani rabo na alheri a lahira, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai yi magana da su ba, kuma ba zai dube su ba, sannan ba zai tsarkake su daga zunubansu ba, kuma suna da wata azaba mai raɗaɗi.

Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Wanda ya yi rantsuwa don ya ci wata dukiya da ba tasa ba; to zai haɗu da Allah yana mai fushi da shi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gaskata wannan magana tasa, ya saukar da wannan ayar: "Lalle waɗanda suke musanya alƙawarin Allah da rantse-rantsensu da wani ɗan farashi ƙanƙani…." har zuwa ƙarshen ayar. Abu Wa'il ya ce: Sai Al-Ash'as ɗan Kaisu ya fito gare mu ya ce: Me Baban Abdurrahman yake faɗa muku (yana nufin Ibn Mas'ud)? Sai muka faɗa masa. Sai ya ce: "Gaskiya ya faɗa, a kaina wannan ayar ta sauka. Mun yi rigima da wani mutum a kan wata rijiya, sai muka je gaban Annabi (ﷺ) domin ya yi mana hukunci, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kawo shaidunka biyu, ko kuma shi ya rantse." Sai na ce: In dai haka ne; to fa shi zai rantse ba tare da ya damu ba. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya yi rantsuwa don ya cancanci wata dukiya alhalin ƙarya yake; to zai haɗu da Allah alhalin yana mai fushi da shi." Sai Allah ya gaskata wannan magana, ya saukar da wannan ayar. [Bukhari #2515-2516, da Muslim #136].

Abdullahi ɗan Abu Aufa (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: Wani mutum a kasuwa, ya tsaya a kan hajarsa yana rantsuwar cewa, an saya da kuɗi kaza da kaza, alhalin ƙarya yake, don kawai ya zurma wani Musulmi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar. [Bukhari #2088].

Babu cin karo tsakanin ruwayoyin nan guda biyu, domin zai iya yiwuwa ayar ta sauka a kan ƙissoshin biyu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai halin wasu mutane daga cikin Yahudu da Nasara cewa, idan suna karanta littafin da aka saukar musu, sai su riƙa karkata harshensu suna jirkita wasu lafuzan littafin, suna wasa da ma'anoninsa, da nufin ɓatar da muminai, don su zaci cewa maganar Allah ce abin da suke karantawa, alhalin ba ita ba ce; kawai wannan wata bidi'a ce suka shigo da ita a cikin addini. Da wannan aiki nasu, suna yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ƙarya ne tare da suna sani. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba abu ne mai yiwuwa ba, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zaɓi wani mutum, ya ba shi littafi da hikima, ya yi masa baiwar annabci, sannan ya riƙa kiran mutane kan su bauta masa ba Allah ba. Idan har Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa wasu bayinsa irin wannan baiwa; to zai umarce su ne da su zamo malamai na Allah, masu aiki da iliminsu, masu ikhlasi da bautar Allah, suna koyar da mutane ilimi da tarbiyya ta ƙwarai, saboda littafin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne suke koyarwa. Hakanan kuma ba zai umarce su su riƙa bauta wa mala'iku ko annabawa ba Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba. Domin babu yadda za a yi ya umarce su da su kafirce wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bayan sun musulunta, sun miƙa wuya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar Annabi Muhammadu (ﷺ) a kan sauran annabawa.

2. Annabawa gaba ɗayansu bayi ne na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), masu bauta masa da bin umarninsa.

3. Idan ya zamana wajibi ne a kan annabawa su yi imani da Annabi (ﷺ); to imanin al'ummominsu da shi ya fi zama wajibi a kansu.

4. Babu wata hanyar samun yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sai ta hanyar bin Manzon Allah (ﷺ), ko da kuwa annabawa ne, da a ce suna da rai lokacin aiko Annabi Muhammad (ﷺ); to sai sun yi imani da shi.

5. Wannan aya tana matsayin martani ga masu cewa Khadir (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana nan da ransa bai mutu ba. Domin da wannan magana gaskiya ce, da ya zama wajibi a kansa ya bayyana a zamanin Annabi (ﷺ), ya yi imani da shi, ya yi jihadi tare da shi, ya taimaka masa.

Suratu Ali-Imran (81-82)

وَإِذۡ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ لَمَآ ءَاتَيۡتُكُم مِّن كِتَٰبٖ وَحِكۡمَةٖ ثُمَّ جَآءَكُمۡ رَسُولٞ مُّصَدِّقٞ لِّمَا مَعَكُمۡ لَتُؤۡمِنُنَّ بِهِۦ وَلَتَنصُرُنَّهُۥۚ قَالَ ءَأَقۡرَرۡتُمۡ وَأَخَذۡتُمۡ عَلَىٰ ذَٰلِكُمۡ إِصۡرِيۖ قَالُوٓاْ أَقۡرَرۡنَاۚ قَالَ فَٱشۡهَدُواْ وَأَنَا۠ مَعَكُم مِّنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ٨١ فَمَن تَوَلَّىٰ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٨٢

81. Kuma ka tuna lokacin da Allah Ya yi alƙawari da annabawa cewa: "Duk irin abin da Na ba ku na littafi da wata hikima, sannan sai wani Manzo ya zo muku mai gaskata abin da yake tare da ku, to lalle ku yi imani da shi, kuma lalle ku taimake shi." Ya ce: "Shin kun yarda da hakan, kuma kun ɗauki alƙawarina a kan hakan?" Suka ce: "Mun yarda da haka." Ya ce: "To ku shaida, kuma Ni ma Ina tare da ku cikin masu shaidawa."

82. To duk wanda ya juya baya bayan wannan, to waɗannan sune fasiƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da Annabinsa (ﷺ) lokacin da ya ɗauki alƙawari mai ƙarfi tsakaninsa da annabawa cewa, duk da annabcin da ya aiko su da shi da littattafai da hikima da ya ba su, sannan daga baya ya aiko da wani manzo ya zo musu, su da al'ummominsu, yana tabbatar da gaskiyar da suka zo da ita, to wajibi ne su yi imani da shi su gaskata abin da ya zo da shi, su taimaka masa. Ana nufin Manzon Allah Muhammadu (ﷺ).
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara ƙarfafa musu cewa, sun yarda da wannan alƙawari, kuma sun riƙe shi da ƙarfi?! Dukkansu suka amsa da cewa, sun yarda kuma sun tabbata. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kafa su da su zama masu shaidar kansu da kansu a kan haka da kuma al'ummominsu. Duk kuma wanda ya bijire bayan wannan alƙawari da ya ɗauka; to masu yin haka su ne fasiƙai, waɗanda suka fita daga ɗa'ar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya kara masa yarda) ya ruwaito cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Da a ce ɗan'uwana Musa yana nan da ransa, da babu abin da zai fisshe shi, dole sai yi min biyayya." [Ahmad #5195].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Musulunci shi kaɗai ne addini a wurin Allah. Wanda ya bi wani addini ba Musulunci ba; to Allah ba zai kaɓe shi daga wurinsa ba.

2. Dole ne a kan duk wani mai furuci, ya furta imaninsa da Allah da bakinsa, kamar yadda yake wajibi a kansa ya ƙudurce a zuciyarsa.

3. Imani da Allah shi ne asali, duk sauran abubuwa da bawa yake imani da su rassa ne nasa, shi ya sa Allah ya gabatar da shi a nan.

Suratu Ali-Imran (83-85)

أَفَغَيۡرَ دِينِ ٱللَّهِ يَبۡغُونَ وَلَهُۥٓ أَسۡلَمَ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ طَوۡعٗا وَكَرۡهٗا وَإِلَيۡهِ يُرۡجَعُونَ ٨٣ قُلۡ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ عَلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمۡ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ٨٤ وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٨٥

83. To shin yanzu wani addini suke nema ba na Allah ba, alhalin duk wanda yake cikin sammai da ƙasa gare Shi ne ya miƙa wuya yana so ko yana ƙi, kuma zuwa gare Shi za a komar da su?

84. Ka ce: “Mun yi imani da Allah da abin da aka saukar mana da kuma abin da aka saukar wa Ibrahimu da Isma’ila da Ishaƙa da Ya’aƙubu da jikokin Ya’aƙubu, da abin da aka ba wa Musa da Isa da abin da aka ba wa annabawa daga Ubangijinsu; ba ma nuna bambanci a kan ɗaya daga cikinsu, kuma mu muna masu miƙa wuya gare Shi.”
85. Duk kuma wanda ya nemi (bin) wani addini ba Musulunci ba, to har abada ba za a karɓa daga gare shi ba, kuma shi a lahira yana cikin hasararru.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, duk wanda ya nemi wani addini ba Musuluncin da Allah ya aiko Annabinsa Muhammad (ﷺ) da shi ba; to ya yi aikin banza. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sukar duk wanda ya nemi wani addini ba na Allah ba, kuma ba shari’arsa ba, alhalin duk waɗanda suke sama da waɗanda suke ƙasa, gare shi suka miƙa wuya, sun so hakan, ko ba su so ba, duk suna ƙarƙashin ikonsa ne, shi ne mai sarrafa su yadda ya ga dama. Kuma idan suka mutu zuwa gare shi ne makomarsu take, zai yi wa kowa hisabi da gwargwadon aikinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya fuskantar da maganarsa zuwa ga Annabi (ﷺ), yana umartar sa da ya gaya wa waɗanda suke neman wani addini daban ba Musulunci ba cewa, mu mun yi imani da Allah da Alƙur’anin da aka saukar mana, da kuma sunna, da duk abin da Allah ya saukar wa annabawansa, Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ‘ya’yansa, Annabi Isma’ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Is’haƙa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da Annabi Yaƙuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ɗan Annabi Is’haƙa, da kuma abin da aka saukar wa annabawan Banu Isra’ila, waɗanda suka fito daga zurriyar ‘ya’yan Annabi Yaƙubu, su goma sha biyu. Hakanan mun yi imani da littafin Attaura da Allah ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da littafin Linjila da Allah ya saukar wa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kuma mu’ujizojin da Allah ya ba su domin tabbatar da gaskiyarsu. Mun yi imani da duk annabawa gaba ɗayansu, da abin da aka saukar musu na littattafai daga Ubangijinsu, ba za mu bambanta tsakaninsu ba wajen imani, ta hanyar yin imani da wasu, mu kafirce wa wasu; mu gaba ɗayanmu ciki da waje, mun miƙa wuya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ba za mu yarda da wani addini in ba Musulunci ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya bi wani addini ba na Musulunci ba; to ba za a taɓa karɓar sa daga gare shi ba, kuma a lahira yana cikin hasararru, wannan kuma ita ce hasara ta haƙiƙa, domin ya wahalar da kansa a kan abin da bai amfane shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɓacewar mai ilimi ta fi ɓacewar jahili muni.

2. Jahili ya fi saurin miƙa wuya yayin da za a fahintar da shi abin da bai fahinta ba, amma wanda ya sani ya kangare; to wannan yana da wuya ya dawo kan hanya.

3. Tubar bawa ba ta cika, har sai ya gyara ɓarnar da ya yi a baya, ko da ta hanyar bayyana cewa abin da yake kai a baya ɓata ne, don ire-irensa su dawo, su ma su tuba. Ko kuma idan ya ja wasu zuwa ga wannan ɓatan; to dole ne ya bayyana musu abin da suke a kai ɓata ne.

4. Duk wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa wata ni'ima, sannan ya kafirce masa; to Allah na iya karɓe wannan ni'imar daga hannunsa.

5. Wanda ya yi ridda, sannan daga baya ya tuba, ya gyaru; to Allah zai karɓi tubansa a duniya da lahira.

6. Tuba yana kankare laifin da mai tuba ya yi a baya, ko da kuwa kafirci ne.

Suratu Ali-Imran (86-89)

كَيۡفَ يَهۡدِي ٱللَّهُ قَوۡمٗا كَفَرُواْ بَعۡدَ إِيمَٰنِهِمۡ وَشَهِدُوٓاْ أَنَّ ٱلرَّسُولَ حَقّٞ وَجَآءَهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُۚ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٨٦ أُوْلَٰٓئِكَ جَزَآؤُهُمۡ أَنَّ عَلَيۡهِمۡ لَعۡنَةَ ٱللَّهِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلنَّاسِ أَجۡمَعِينَ ٨٧ خَٰلِدِينَ فِيهَا لَا يُخَفَّفُ عَنۡهُمُ ٱلۡعَذَابُ وَلَا هُمۡ يُنظَرُونَ ٨٨ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُواْ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ وَأَصۡلَحُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٨٩

86. Ta yaya Allah zai shiryar da mutanen da suka kafirta bayan imaninsu, kuma bayan sun shaida cewa, Manzon gaskiya ne, kuma hujjoji sun zo musu? Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane azzalumai.

87. Waɗannan sakamakonsu shi ne, la'antar Allah za ta tabbata a kansu da ta mala'iku da mutane gaba ɗaya.

88. Suna masu dawwama a cikinta, ba za a sassauta musu azaba ba, kuma ba za a jinkirta musu ba.

89. Sai fa waɗanda suka sake tuba bayan haka, kuma suka gyara (ayyukansu), to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, ba zai shiryar da mutanen da suka yi ridda ba, suka juya wa Musulunci baya, alhalin da farko sun yi imani, kuma sun tabbatar da cewa, Annabi Muhammad (ﷺ) gaskiya ne, saboda hujjoji bayyanannu, kuma gamsassu, masu ƙara tabbatar da gaskiyarsa. Ta yaya irin waɗannan za su cancanci shiriya? Allah ba ya shiryar da waɗanda suka zalunci kawunansu, ta hanyar barin gaskiya bayan sun fahince ta, suka kama ƙarya bayan sun gane ƙarya ce a fili.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗi uƙubar waɗannan azzaluman a duniya da lahira, wadda ita ce la'anar Allah da mala'iku da duk halittun Allah a kansu, kuma za su ci gaba da zama cikin wannan la'anar, da wannan uƙubar, har abada, kuma ba za a taba sassauta musu azaba ba, kuma ba za a saurara musu ba.
Amma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi togaciya ta waɗanda suka tuba, suka yi ayyuka na ƙwarai, kuma suka gyara kurakuren da suka yi; to waɗannan Allah yana yafe musu, saboda shi mai yawan gafara ne, mai yawan jin ƙai ga bayinsa masu tuba su gyara.

Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: "Wani mutumin Madina ya musulunta, daga baya kuma sai ya yi ridda, ya koma shirka. Sannan ya dawo ya yi nadama, sai ya aika wa mutanensa yana

cewa: ‘Ku tambayar mini Manzon Allah (ﷺ), shin zan iya sake tuba?’ Mutanensa suka sami Manzon Allah (ﷺ), suka faɗa masa cewa: ‘Wane da ya yi ridda ya yi nadama, kuma ya aiko mu mu tambaya masa cewa, shin zai iya sake tuba?” Sai wannan ayar ta sauka: ‘Ta yaya Allah zai shiryar da mutanen da suka kafirta bayan imaninsu...’ har inda ya ce: ‘...to lalle Allah mai gafara ne, mai jin ƙai.’ Sai Annabi (ﷺ) ya aika masa ya zo ya sake shiga Musulunci.” [Nasa’i #4068, da Ahmad #2218].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yadda imani yake ƙaruwa da ayyuka na ƙwarai, haka shi ma kafirci yake hauhawa da ƙaruwar aikata ayyukan kafirci.

2. Tubar mutum ba za ta zama karɓaɓɓiya ba a wurin Allah har sai ya bar laifukan da yake aikatawa, ya kuma gyara abin da ya ɓata a baya.

3. Mummunan aiki yana haddasa wani mummuna irinsa, matuƙar bawa bai dawo kan tafarki madaidaici ba.

4. Wanda ya yi ridda ya bar Musulunci har mutuwa ta zo masa bai tuba ba; to ba za a karɓi tubansa ba a wannan lokacin.

Suratu Ali-Imran (90-91)

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بَعۡدَ إِيمَٰنِهِمۡ ثُمَّ ٱزۡدَادُواْ كُفۡرٗا لَّن تُقۡبَلَ تَوۡبَتُهُمۡ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلضَّآلُّونَ ٩٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَمَاتُواْ وَهُمۡ كُفَّارٞ فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡ أَحَدِهِم مِّلۡءُ ٱلۡأَرۡضِ ذَهَبٗا وَلَوِ ٱفۡتَدَىٰ بِهِۦٓۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٩١

90. Lalle waɗanda suka kafirta bayan imaninsu, sannan suka ƙara zurfi cikin kafirci, to ba za a karɓi tubansu ba, kuma waɗannan su ne ɓatattu.

91. Lalle waɗanda suka kafirta, kuma suka mutu alhali suna kafirai, to ba za a karɓi cikin ƙasa na zinari daga ɗaya daga cikinsu ba, ko da zai fanshi kansa da shi. Waɗannan suna da wata azaba mai raɗaɗi kuma ba su da wasu mataimaka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin uƙubar waɗanda suka yi imani, sannan daga baya suka yi ridda, suka kafirta, sannan suka yi ta ƙara nutsawa cikin kafirci, suka kuma zauna a haka, har suka mutu cewa, Allah ba zai taɓa karɓar tubansu ba, domin su ne suka zaɓi su bar hanyar gaskiya, su bi hanyar ɓata.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar da cewa, waɗanda suka kafirta, kuma suka mutu a kan kafirci, ba su tuba ba; to Allah ba zai karɓi aikin da suka yi ba, ko da kuwa zai yi sadaka da kwatankwacin cikin ƙasa na zinariya domin ya kusanci Allah da wannan sadakar, Allah ba zai karɓa ba, ko kuma ya ce zai fanshi kansa da wannan, to Allah ba zai karɓa ba. Sakamakon waɗannan a lahira shi ne azabar wuta mai raɗaɗi, kuma babu wanda ya isa ya kuɓutar da su daga wannan azabar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitar da muminai a kan su nemi alheri, ta hanyar gabatar da soyayyarsu ga Allah a kan soyayyarsu ga dukiyoyinsu. Yayin da suka haƙura da abin da ransu yake so, suka fitar da dukiyarsu suka bayar don Allah; to zukatansu za su tsarkaka daga cutar rowa da bautar dukiya.

2. Abin da yake shiga rai sosai shi ne mutum ba ya son rabuwa da shi, don haka bayar da shi sadaka yana nuna ƙarfin imanin mai yin hakan.

3. Yayin da mawadata za su riƙa bayar da dukiyarsu da suke so ga talakawa, wannan zai kawo gyaruwar al'umma, kuma ya ƙara danƙon zumunta tsakanin mawadata da talakawa marasa abin hannu, sai rayuwa ta yi kyau ga kowa da kowa.

4. Yin sadaka don Allah, domin Allah ya san komai da ke cikin zukatan bayinsa, kuma zai yi musu sakayya gwargwadon abin da suka ƙudurce na ikhlasi ko rashinsa.

5. Allah ya neme mu da mu ciyar da wani abu na dukiyarmu wanda muke so, ba duka ba. Wannan yana daga cikin rahamar Allah da tausayinsa ga bayinsa, wajen ɗora musu abin da za su iya ɗauka, ba wanda zai gagare su ba.

Suratu Ali-Imran (92)

لَن تَنَالُواْ ٱلۡبِرَّ حَتَّىٰ تُنفِقُواْ مِمَّا تُحِبُّونَۚ وَمَا تُنفِقُواْ مِن شَيۡءٖ فَإِنَّ ٱللَّهَ بِهِۦ عَلِيمٞ ٩٢

92. Ba za ku taɓa dacewa da aiki na alheri ba har sai kun ciyar daga abin da kuke so, kuma abin da duk kuka ciyar kowane iri ne, to lalle Allah Yana sane da shi.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a ayar baya ya yi bayanin cewa, ba zai karɓi sadakar kafiri ba, ko da zai ciyar da kwatankwacin cikin duniya na zinari, don ya kuɓutar da kansa daga azabar Allah a ranar alƙiyama, sai a wannan ayar Allah yake kwaɗaitar da muminai kan su ciyar da dukiyarsu, kuma ya bayyana cewa, abin da ya fi son bawa ya yi sadaka da shi, shi ne abin da shi ya fi so; wannan ne zai kai shi matakin samun alheri mai yawa. Allah yana cewa: "Ba za ku kai ga samun alheri mai yawa ba daga Allah, har sai kun yi sadaka da dukiyar da kuke ƙauna a zukatanku. Duk abin da kuka ciyar na dukiyarku; to Allah ya sani, kuma a ranar lahira zai saka wa wanda ya yi haka da cikakken sakamako."

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Abu Ɗalha mutumin Madina ne mai yawan dukiya; abin da kuma ya fi ƙauna cikin dukiyarsa ita ce gonarsa mai suna *Bairuha,* tana kallon masallacin Annabi (ﷺ). Hasali ma Annabi (ﷺ) yakan shiga cikinta ya sha ruwanta mai daɗi. To lokacin da wannan ayar ta sauka, sai Abu Ɗalha ya ce: 'Ya Manzon Allah, Allah yana cewa: 'Ba za ku taɓa dacewa da aiki na alheri ba, har sai kun ciyar daga abin da kuke so...', ni kuma a cikin dukiyata na fi son *Bairuha*, don haka na bayar da ita sadaka don Allah, ina fatan samun alherinta da ajiyayyen ladanta a wurin Allah Ta'ala, don haka ya Ma'aikin Allah, ka saka ta inda Allah Ta'ala ya nuna maka.' Sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Taɓdi! Wannan fa dukiya ce mai riba, wannan dukiya ce mai riba; to lalle na ji abin da ka ce, amma ni ina ganin ka yi kyautar ta ga danginka mafi kusanci da kai shi ya fi riba." Sai Abu Ɗalha ya ce: 'Zan yi hakan, ya Ma'aikin Allah.' Sai Abu Ɗalha ya raba wa danginsa da 'ya'yan baffanninsa wannan gonar." [Bukhari #2769, da Muslim #998, da Ahmad #12461].

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Martani ga Yahudawa masu ƙaryata samuwar shafe hukunci a sharia, wato *nasku*

2. Umartar su da su ɗauko Littafin Attaura su karanta, wata hanya ce ta kafa wa abokin husuma hujja da abin da ya yi imani da shi kuma ya yarda da shi, wadda ba ta yadda zai iya kauce mata.

3. Umartar su da cewa su karanta su da kansu, bai ce 'mu karanta' ba, domin idan da Musulmi ne za su karanta, suna iya cewa ba su yarda ba, su riƙa tuhumar Musulmi cewa sun yi ƙari ko ragi a cikin karatun. Don haka su suka karanta da kansu, suka kuma ga gaskiyar a fili.

4. Kira zuwa ga bin gaskiya, domin duk sa'adda gaskiya ta bayyana a fili, kuma mutum ya kauce mata; to wannan ya tabbata babban azzalumi. Domin babu zaluncin da ya kai a kirawo shi zuwa ga hukunci da Littafin Allah, sannan ya bijire, saboda girman kai da kangara.

5. Mayar da martani ga Yahudawa masu da'awar suna bin addinin Annabi Ibrahimu, amma kuma suna jayayya da Musulmi a kan an halatta musu wasu abubuwa da su aka haramta musu a cikin Littafin Attaura. Domin ai addinin Annabi Ibrahimu bai haramta abubuwan da su aka haramta musu su a cikin Attaura ba. Don haka Musulmi su ne masu bin Addinin Annabi Ibrahimu na gaskiya.

Suratu Ali-Imran (93-94)

*كُلُّ ٱلطَّعَامِ كَانَ حِلًّا لِّبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ إِلَّا مَا حَرَّمَ إِسۡرَٰٓءِيلُ عَلَىٰ نَفۡسِهِۦ مِن قَبۡلِ أَن تُنَزَّلَ ٱلتَّوۡرَىٰةُۚ قُلۡ فَأۡتُواْ بِٱلتَّوۡرَىٰةِ فَٱتۡلُوهَآ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٩٣ فَمَنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٩٤

93. Duk wani abinci ya kasance halal ne ga Banu Israila sai abin da shi Isra'ilu ya haramta wa kansa tun kafin a saukar da Attaura. Ka ce: "To ku zo da Attaura, sai ku karanta ta in kun kasance masu gaskiya."

94. To duk wanda ya ƙirƙiri ƙarya ya jingina wa Allah bayan wannan, to waɗannan su ne azzalumai.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a waɗannan ayoyi yana ba da labarin cewa, kafin a saukar da Attaura ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), duk wani nau'i na abinci halal ne ga Banu Isra'ila su ci, sai nau'i guda ɗaya wanda shi Isra'ilu, wato Annabi Ya'aƙubu ya haramta wa kansa, ba Allah ne ya haramta masa ba, sannan daga baya 'ya'yansa su ma suka yi koyi da shi, suka haramta wa kawunansu cin wannan nau'i na abinci. Wannan kuwa shi ne naman raƙuma da nononsu. To bayan saukar da Attaura, sai Allah ya haramta musu abin da ya ga dama a cikinta, ya kuma halatta musu abin da ya ga dama. Don haka wannan hukuncin ya shafe wancan hukunci na halatta musu komai, sai raƙuma da nononsu. Sai Allah Ta'ala ya umarci Annabinsa da ya nemi Yahudawa su ɗauko littafin Attaura su karanta idan abin da suke faɗa gaskiya ne, wanda kuma ba za su gan shi ba. To bayan Allah ya tsayar musu da hujja, sai ya faɗa musu cewa, duk wanda ya kuskura ya yi masa ƙarya bayan wannan bayanin da suka ji; to waɗannan su ne azzalumai.

Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) yana cewa: Wata ƙungiyar Yahudawa sun je gaban Annabi (ﷺ) suka ce: "Ya Baban Alƙasim, za mu tambaye ka wasu abubuwa, ka ba mu amsarsu, domin babu wanda ya san su sai annabi." Daga cikin abin da suka tambaye shi, sun ce: "Wane abinci ne Isra'ilu (Ya'aƙubu) ya haramta wa kansa tun kafin a saukar da Attaura?" Sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Na haɗa ku da Allah, shin kun san cewa, Isra'ilu (Annabi Ya'aƙubu) ya daɗe yana rashin lafiya mai tsanani, sai ya yi

bakance na cewa, idan Allah ya ba shi lafiya to zai haramta wa kansa abin shan da ya fi so da abincin da ya fi so, kuma abincin da ya fi so shi ne naman raƙuma, abin shan da ya fi so kuma shi ne nononsu?" Sai Yahudawan nan suka ce: "Gaskiya ne, haka ne." [Ahmad #2471, da Tafsirin *Tabari* #7420, da *Almu'ujamul Kabir* 12:246 #13012].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɗakin Ka'aba shi ne farkon ɗaki da Allah ya tanade shi a bayan ƙasa don ibada. Don haka wajibi ne a kan kowane Musulmi ya girmama shi.

2. Wajibi ne a kan kowane Musulmi da Allah ya hore masa damar zuwa hajji, ya gaggauta zuwa, kada ya yi jinkiri.

3. Allah cikakken mawadaci ne, ba shi da buƙatar komai a wurin halittunsa, amma duk halittunsa mabuƙata ne a wajensa.

4. Allah ba ya farlanta wa bayinsa abin da ya fi ƙarfinsu. Duk wani umarni ko hani da Allah zai nemi bawansa da shi to sai idan ya san yana da iko a kansa, idan ba shi da iko; to ya faɗi daga kansa.

Suratu Ali-Imran (95-97)

قُلْ صَدَقَ ٱللَّهُ ۗ فَٱتَّبِعُوا۟ مِلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفًا ۖ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٩٥﴾ إِنَّ أَوَّلَ بَيْتٍ وُضِعَ لِلنَّاسِ لَلَّذِى بِبَكَّةَ مُبَارَكًا وَهُدًى لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿٩٦﴾ فِيهِ ءَايَٰتٌۢ بَيِّنَٰتٌ مَّقَامُ إِبْرَٰهِيمَ ۖ وَمَن دَخَلَهُۥ كَانَ ءَامِنًا ۗ وَلِلَّهِ عَلَى ٱلنَّاسِ حِجُّ ٱلْبَيْتِ مَنِ ٱسْتَطَاعَ إِلَيْهِ سَبِيلًا ۚ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِىٌّ عَنِ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٩٧﴾

95. Ka ce: "Allah Ya yi gaskiya. Don haka ku bi addinin Ibrahimu, mai karkace wa ɓarna, kuma bai taɓa zama ɗaya daga cikin mushirikai ba."

96. Lalle farkon ɗaki da aka tanada don mutane (su yi ibada a cikinsa) shi ne wanda yake cikin Bakka, (ɗaki ne) mai albarka, kuma shiriya ne ga talikai.

97. A cikinsa akwai ayoyi bayyanannu, (kuma akwai) Maƙamu Ibrahimu; wanda duk ya shige shi ya zama amintacce. Kuma Allah Ya wajabta wa mutane ziyarar wannan ɗakin ga wanda ya sami iko. Wanda kuwa ya kafirce, to lalle Allah Mawadaci ne ga barin talikai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya ce wa Yahudawa, duk abin da Allah ya labarta ko ya shar'anta na hukunci; to gaskiya ne, kamar abin da ya faɗa musu cewa, babu wani abin da Allah ya haramta musu kafin saukar da Attaura, sai nau'i biyu, watau naman raƙumi da nononsa. Don haka su zo su bi addinin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), idan har su masu gaskiya ne game da tutiyar su ta cewa su jikokinsa ne; domin shi mai kaɗaita Allah ne, ba ya shirka, ba ya kuma tare da masu yin ta.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, farkon ɗakin da aka gina shi domin mutane su bauta masa a cikinsa, kuma su yi ɗawafi su yi salla, su yi i'itikafi shi ne Ɗakin Ka'aba. Ɗakin Allah ne mai alfarma da ke garin Makka, mai ɗimbin albarka da abubuwan amfani masu yawa, na addini da na rayuwa, kamar riɓanyar lada a wurinsa da kuma arziki mai ɗimbin yawa da Allah ya kawo a garin, kuma shiriya ne ga ɗaukacin talikai, musamman zamantowarsa alƙibla ga Musulmi baki ɗaya lokutan sallolinsu. Kuma shi ne wurin hajjinsu da umararsu. To amma Yahudawa da Nasara masu tutiyar su ne a kan

addinin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai ga shi ba sa zuwa Ɗakin da ya gina domin aikin hajji da umara, wanda hakan yake nuna sun yi hannun riga da shi, ba su ba addininsa.

An karɓo daga Abu Zarri (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Na tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa: “Wane masallaci aka fara ginawa a bayan ƙasa?” Sai ya ce: “Masallaci mai alfarma.” Sai na ce: “Sai kuma wanne?” Sai ya ce: “Masallacin Kudus.” Sai na ce: “Shekaru nawa ne a tsakaninsu?” Sai ya ce: “Shekaru arba’in. Sannan duk inda salla ta kama ka bayan haka; to ka fuskance shi a sallarka, a nan falalar take.” [Bukhari #3366, da Muslim #520].

A cikin wannan Ɗakin akwai dalilai bayyanannu masu nuna kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da hikimarsa da adalcinsa da girman Kudirarsa da sauran siffofinsa maɗaukaka, da kuma wasu alamomi masu nuna girman darajar wannan Ɗakin, daga cikinsu har da wuraren da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tsaya domin aikin hajji, kuma duk wanda ya shiga cikinsa; to ya aminta daga duk wani abin ƙi. Allah ya farlanta zuwa wannan Ɗaki domin gabatar da aikin hajji ga duk wanda Allah ya ba shi iko, na lafiya da guziri da abin hawa. Amma duk wanda ya ƙaryata hajji ko ya bijire, to ya sani Allah mawadaci ne, ba ya buƙatar hajjinsa, ba ya ma da buƙata a wurin dukkan talikai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Fito da haƙiƙanin su wane ne Ma’abota Littafi da fito da siffofinsu a fili a gane su. Suna nuna su masu riƙo da addini ne, alhalin ƙarya suke, sun riga sun kafirce wa ayoyin Allah na Alƙur’ani. Wanda duk ya kafirce wa wani abu daga littafin Allah; to ya kafirce wa littafin ne gaba ɗayansa. Da a ce sun yi imani da abin da ya zo a cikin littafinsu, to da sun yi imani da duk wani annabi da aka aiko bayan annabinsu. Domin addini a haƙiƙaninsa guda ɗaya ne, wanda duk ya fahimci addinin gaskiya; to duk wani addini da ya zo daga Allah, zai fahimce shi ya karɓe shi.

2. Faɗar cewa Allah yana ganin duk abin da suke aikatawa, kuma shi ba rafkananne ne game da ayyukansu ba, wannan shi zai razana ya firgita duk wani mayaudarin mutum, kafiri, ɓatacce mai ɓatarwa.

3. Hanyar Allah miƙaƙƙiya ce ɗoɗar, ba ta da wata karkata ko kaɗan; duk kuma wata hanya wadda ba ta Allah ba; to karkatacciya ce.

4. Allah ya zargi masu kange wanda ya yi imani su hana shi bin hanyar gaskiya, tare da cewa sun hana kafirai ma bin gaskiyar, domin karkatar da mumini daga Musulunci zuwa ga kafirci ya fi muni fiye da karkatar da kafiri, domin da ma shi a karkace yake, saɓanin mumini wanda shi raba shi da gaskiya aka yi, aka ingiza shi cikin kafirci; wannan kuwa ya fi muni a wurin Allah.

Suratu Ali-Imran (98-99)

قُلْ يَـٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَـٰبِ لِمَ تَكْفُرُونَ بِـَٔايَـٰتِ ٱللَّهِ وَٱللَّهُ شَهِيدٌ عَلَىٰ مَا تَعْمَلُونَ ﴿٩٨﴾ قُلْ يَـٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَـٰبِ لِمَ تَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ مَنْ ءَامَنَ تَبْغُونَهَا عِوَجًا وَأَنتُمْ شُهَدَآءُ ۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَـٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ﴿٩٩﴾

98. Ka ce: “Ya ku Ma’abota Littafi, don me kuke kafirce wa ayoyin Allah, kuma alhalin Allah Mai ba da shaida ne ga abin da kuke aikatawa?”

99. Ka ce: “Ya ku Ma’abota Littafi, don me kuke kange wanda ya yi imani daga hanyar Allah, kuna son ta zamo karkatacciya, kuma alhali ku da kanku masu shaida ne, kuma Allah ba gafalalle ne game da abin da kuke aikatawa ba?”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabinsa (ﷺ) da ya tambayi Yahudawa da Nasara, me ya sa suke musanta hujjojin da Allah ya saukar da su a littattafansu masu ɗauke da tabbatar da gaskiyar annabcin Annabi (ﷺ) da gaskiyar abin da ya zo da shi, tare da sun san cewa babu wani aikinsu da zai ɓuya a wurin Allah? Allah yana ganin duk irin ayyukan da suke yi.
Kuma ya umarce shi da ya ƙara tambayar Yahudawa, me ya sa suke ƙoƙarin ɓatar da muminai daga kan hanyar Allah, suke kuma ƙoƙarin su ga wannan hanyar ta gaskiya ta karkace, alhalin sun san gaskiyar, kuma sun san munin abin da suke aikatawa? To su sani Allah ba rafkananne ne game da abin da suke aikatawa ba, yana sane da komai, kuma duk zai yi musu hisabi a kai ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗin Musulmi a kan su yi hattara wajen yarda da maganganun Yahudawa da Nasara da aiki da su, ko kwaikwayon wani tsari nasu na rayuwa, domin zukatansu cike suke da hassada da ƙullata ga Musulmi, a kullum suna tunanin hanyar da za su bi su raba Musulmi da addininsu, su mayar da su kafirai. Don haka idan Musulmi suka yi sakaci suka karɓi tsare-tsarensu na rayuwa; to za su iya kai su ga halaka.
2. Sanin falalar sahabban Manzon Allah (ﷺ), ta kasancewarsa ya rayu a cikinsu, kuma sun gan shi, sun ga hasken annabci da yake ɗauke da shi, kuma ya zame musu ƙaƙƙarfar katanga mai kare su daga faɗawa kafirci ko karkace hanyar gaskiya. Wannan ba ƙaramar falala ba ce ga sahabbai; babu wanda ya sami irinta cikin wannan al’umma sai su.

3. Riƙo da littafin Allah da sunnar Annabi (ﷺ) shi ne babban abin da zai tsare mumini daga kauce wa hanyar Allah, ko faɗawa cikin kafirci.

4. Idan zaman Annabi (ﷺ) a cikin wannan al’umma ya ƙare lokacin rayuwarsa, to ai ayoyin Allah da sunnonin Annabinsa suna nan a tsakanin al’umma, kuma Musulmi a yau ana neman su da aiki da Alƙur’ani da sunna, kamar irin yadda aka nemi musulmin farko da hakan; don haka har yanzu hanyar samun kariya da tsari a fili take.

Suratu Ali-Imran (100-101)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تُطِيعُواْ فَرِيقٗا مِّنَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ يَرُدُّوكُم بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡ كَٰفِرِينَ ١٠٠ وَكَيۡفَ تَكۡفُرُونَ وَأَنتُمۡ تُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ وَفِيكُمۡ رَسُولُهُۥۗ وَمَن يَعۡتَصِم بِٱللَّهِ فَقَدۡ هُدِيَ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ١٠١

100. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka bi wani ɓangare na waɗanda aka ba wa Littafi, to za su mayar da ku kafirai bayan imaninku.

101. Ta yaya kuma za ku kafirce, ga shi kuwa ana karanta muku ayoyin Allah, kuma Manzonsa yana tare da ku? Duk kuwa wanda ya riƙi Allah, to haƙiƙa an shiryar da shi tafarki madaidaici.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gargaɗin muminai da cewa, idan suka kuskura suka nuna biyayyarsu ga Yahudawa da Nasara, waɗanda suke yi musu hassadar Alƙur’ani da Allah ya ba su da falalar Musulunci; to tabbas za su raba su da imaninsu, su mayar da su kafirai suna ji suna gani. Amma Allah ya nuna cewa, da wahala ƙwarai muminai su yarda su koma kafirci bayan ga Alƙur’ani nan kullum

suna ji ana karanta musu ayoyinsa, sannan ga Manzon Allah nan a tsakaninsu, yana isar musu duk wani saƙo da aka saukar dominsu. Shi imani idan har ya ratsa ƙoƙon zuciya; to abu ne mai wuyar gaske a iya cire shi, sai dai wani iko na Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu wata hanya wadda idan suka bi ta, za su tsare kawunansu daga faɗawa ramin kafirci. Wannan hanya ita ce, riƙe Allah da dogaro da shi, domin shi ne madogara ta samun shiriya. Duk wanda ya koma ga Allah a cikin kowanne hali nasa, ya nemi mafaka a wurinsa, ya dogara da shi dogaro na gaskiya, ya riƙe addininsa; to haƙiƙa wannan an shiryar da shi ga hanya miƙaƙƙiya ɗoɗar, wadda babu karkata ko kaɗan a cikinta, ita ce za ta yi masa jagoranci har ta kai shi gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi a kan Musulmi su ƙanƙame ma addinin Musulunci, kar su rabu da shi har zuwa mutuwarsu.

2. Wajibi ne Musulmi su haɗa kai su zama al'umma ɗaya. Hanyar haɗa kan kuma ita ce riƙe shari'ar Allah, wadda take ƙunshe cikin Alƙur'ani da sunnar Annabi (ﷺ). Saɓanin haka kuma shi ne rarrabuwa, wadda take nufin riƙe bidi'o'i da son zuciya.

3. Tunowa da ni'imomin Allah ga bayinsa, waɗanda suka shafi addininsu ko rayuwarsu ta duniya, da gode wa Allah a kansu a zukata da harshe, wannan zai ƙara musu son Allah, sai shi kuma ya ƙara musu falalarsa da kyautarsa.

4. Kira zuwa ga addinin Allah wani ginshiƙi ne na tabbatar da tsarin Allah a bayan ƙasa da kuma murƙushe ƙarya da ɓarna da kawar da mummunan aiki da tabbatar da kyakkyawa. To masu irin wannan aiki su ne masu rabauta duniya da lahira.

Suratu Ali-Imran (102-109)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ حَقَّ تُقَاتِهِۦ وَلَا تَمُوتُنَّ إِلَّا وَأَنتُم مُّسۡلِمُونَ ١٠٢ وَٱعۡتَصِمُواْ بِحَبۡلِ ٱللَّهِ جَمِيعٗا وَلَا تَفَرَّقُواْۚ وَٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ
عَلَيۡكُمۡ إِذۡ كُنتُمۡ أَعۡدَآءٗ فَأَلَّفَ بَيۡنَ قُلُوبِكُمۡ فَأَصۡبَحۡتُم بِنِعۡمَتِهِۦٓ إِخۡوَٰنٗا وَكُنتُمۡ عَلَىٰ شَفَا حُفۡرَةٖ مِّنَ ٱلنَّارِ فَأَنقَذَكُم مِّنۡهَاۗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ
ٱللَّهُ لَكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ١٠٣ وَلۡتَكُن مِّنكُمۡ أُمَّةٞ يَدۡعُونَ إِلَى ٱلۡخَيۡرِ وَيَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ
ٱلۡمُفۡلِحُونَ ١٠٤ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ تَفَرَّقُواْ وَٱخۡتَلَفُواْ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ١٠٥ يَوۡمَ تَبۡيَضُّ وُجُوهٞ وَتَسۡوَدُّ
وُجُوهٞۚ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱسۡوَدَّتۡ وُجُوهُهُمۡ أَكَفَرۡتُم بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡ فَذُوقُواْ ٱلۡعَذَابَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡفُرُونَ ١٠٦ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱبۡيَضَّتۡ وُجُوهُهُمۡ فَفِي
رَحۡمَةِ ٱللَّهِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١٠٧ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ نَتۡلُوهَا عَلَيۡكَ بِٱلۡحَقِّۗ وَمَا ٱللَّهُ يُرِيدُ ظُلۡمٗا لِّلۡعَٰلَمِينَ ١٠٨ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي
ٱلۡأَرۡضِۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ ١٠٩

102. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi taƙawa ga Allah haƙiƙanin taƙawa, kuma lalle kada ku mutu face kuna Musulmi.

103. Kuma ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗaya, kada kuma ku rarraba. Kuma ku tuna ni'imar Allah da Ya yi muku yayin da kuka zamo abokan gaban juna sai Ya haɗa tsakanin zukatanku, sai kuka zamo 'yan'uwan juna a sakamakon ni'imarsa, a da kuma kun kasance a kan gaɓar ramin wuta sai Ya tserar da ku daga gare ta. Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyinsa don ku shiriya.

104. A cikinku lalle a sami wata al'umma waɗanda suke kira zuwa ga alheri, kuma suke umarni da kyakkyawa, kuma suke hana mummuna. Waɗannan su ne masu rabauta.

105. Kuma kada ku kasance kamar waɗanda suka rarrabu, kuma suka sassaba bayan hujjoji sun zo musu. Waɗannan kuwa suna da azaba mai girma.

106. Ranar da waɗansu fuskoki za su yi fari, waɗansu fuskokin kuma za su yi baƙi. Amma waɗanda fuskokinsu suka yi baƙi, (za a ce da su): “Shin ku ne kuka kafirce bayan imaninku? To ku ɗanɗani azaba, saboda kafircin da kuka kasance kuna yi.”

107. Amma waɗanda fuskokinsu suka yi fari kuwa, to suna cikin rahamar Allah, suna masu dawwama a cikinta.

108. Waɗannan ayoyin Allah ne Muke karanta maka su da gaskiya. Kuma Allah ba Ya nufin zalunci ga talikai.

109. Kuma duk abin da yake cikin sammai da ƙasa na Allah ne. Kuma zuwa ga Allah ne ake mayar da duk al’amura.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar bayinsa muminai da su kiyaye dokokinsa gwargwadon ikonsu, sannan su ci gaba da riƙe wannan addini ƙam-ƙam har mutuwa ta zo musu. Kuma lalle su haɗa kansu, su zama abu guda a kan gaskiya, su taru su riƙe igiyar Allah, wadda ita ce Alƙur’anin da Manzo ya zo musu da shi da sunnarsa; kada su yarda su rarrabu.

An karɓo daga Abu Huraira ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Lalle Allah ya yarje muku abubuwa uku, kuma ya ƙi muku abubuwa uku. Ya yarje muku da ku bauta masa, kuma kada ku haɗa komai da shi, kuma duk ilahirinku ku yi riƙo da igiyar Allah, kada ku rarrabu, kuma ya ƙi muku bin jita-jita da yawan tambaya da ɓarnata dukiya.” [Muslim #1715].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su tuna ni’imarsa da ya yi musu lokacin da suka haɗu a kan Musulunci, suka zama ‘yan’uwan juna, bayan a da kafin zuwan Musulunci a rarrabe suke, suna gaba da faɗa da junansu a kan abin da bai taka kara ya karya ba, sai ga shi Allah ya haɗa zukatansu gaba ɗaya sun zama ‘yan’uwa masu ƙaunar junansu, kamar yadda ya bayyana hakan a *Suratul Anfali*, aya ta 62-63.
Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da su cewa, suna dab da faɗawa ramin wuta, sai Allah ya ceto su, domin babu abin da ya rage musu su faɗa cikinta sai mutuwa idan har suna cikin wannan hali na kafirci. To kamar irin wannan bayani da ya yi musu filla-filla har suka fahimta; to haka yake fayyace musu sauran ayoyin nasa, don su zame musu fitilar gane hanyar shiriya da gaskiya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa da cewa, lalle a sami wata ƙungiya daga cikinsu, waɗanda za su ɗauki nauyin yin umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna a cikin al’umma; wannan shi ne maganin rabuwar kai a tsakaninsu. Domin duk al’ummar da take rayuwa kara-zube, kowa yana yin abin da ya ga dama, babu mai tsawata masa yayin da ya yi ba daidai ba, to wannan al’umma za ta rasa haɗuwar kai a tsakanin ‘ya’yanta, domin soye-soyen zukatan mutane mabambanta ne. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda suka siffantu da sifar nan ta umarni da kyakkyawan abu, da hana mummuna, su ne masu samun babban rabo a duniya da lahira.

An karɓo daga Huzaifa ɗan Alyaman (Allah ya kara masa yarda) ya ce, Annabi (ﷺ) ya ce: “Na rantse da wanda raina yake hannunsa, Wallahi, ko dai ku yi umarni da kyakkyawan aiki, ku hana mummuna, ko

kuma ba da daɗewa ba Allah ya aiko muku da wata uƙuba daga gare shi, ku yi ta addu'a ya ƙi amsa muku!" [Ahmad #23349, da Tirmizi #2169].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana muminai rarrabuwa, kamar yadda Yahudu da Nasara a gabaninsu suka rarraba a addininsu, bayan hujjoji bayyanannu sun zo musu. To waɗannan suna da wata babbar azaba daga Allah, a ranar da fuskokin 'yan Aljanna za su yi fari, fuskokin 'yan wuta kuma su yi baƙi. Sai cikin zargi a ce wa masu baƙaƙen fuskoki: "Shin ku ne kuka kafirce bayan imaninku? To ku ɗanɗani azaba saboda kafircinku." Amma masu fararen fuskoki, za su kasance ne a cikin rahamar Allah, tare da jin daɗin da Allah ya tanadar musu a Aljanna na ni'imomi masu yawa, za su ci gaba da rayuwa a cikinsu har abada.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Annabinsa (ﷺ) cewa; waɗancan ayoyi da ya karanta masa su ne gaskiya, kuma tabbas Allah ba wanda yake zalunta cikin halittunsa. Duk abubuwan da suke cikin sammai, da waɗanda suke ƙasa na Allah ne shi kaɗai, kuma duk al'amura gaba ɗaya gare shi za a mayar da su ranar alƙiyama, domin ya saka wa kowa aikin da ya yi; idan ya aikata alheri, ya ga alheri, idan kuwa sharri ya aikata, to ya ga sharri.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ayar farko tana nuna falalar sahabban Annabi (ﷺ) da fifikonsu a cikin wannan al'umma. Duk da cewa ayar ta haɗa har da sauran muminai waɗanda suka zo bayan sahabbai, sai dai sahabban ne aka fara fuskanta da ita, shi ya sa suka fi cancanta da ita. Sannan siffar umarni da kyakkyawan aiki, da hana mummunan aiki da siffar imani da Allah, duk sun fi bayyana tare da sahabbai fiye da sauran muminai da za su zo bayansu.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mafi alherin mutane su ne na ƙarnina, sannan waɗanda suke bi musu, sannan waɗanda suke bi musu...." [Bukhari #3651].

2. Ya kamata al'ummar Musulmi su fahimci cewa, su ne fiyayyu a cikin duk wata al'umma da aka taɓa yi a bayan ƙasa, don su fahimci ƙimarsu da darajarsu, kuma su gane cewa, sun fito ne don su ja ragamar tafiyar wannan al'umma. Kuma nufin Allah shi ne alheri ya yi jagoranci a bayan ƙasa ba sharri ba, don haka ya kamata su zama koyaushe su ne masu bayarwa, ba masu karɓa ba. Kuma abin da za su bayar na aƙida da ilimi da halayya da tsarin rayuwa ya zama mai inganci ne.

3. Fahimtar cewa umarni da kyakkyawan aiki da hana mummunan aiki abu ne mai girman matsayi a addinin Musulunci, domin shi ne tubalin ginin fifikon wannan al'umma a kan sauran al'ummomi.

4. Himmatuwa da samar da ingantaccen imani da Allah a zuciya, domin sai da shi ne za a yi umarni da kyakkyawa, a hana mummuna, saboda shi ne sahihin ma'auni na tantance abu mai kyau da mummuna.

5. Fifita wannan al'umma da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi a kan sauran al'ummomi, saboda siffantuwarsu ne da umarni da kyakkyawa da hani da mummuna. Hakan yana nuna wannan siffar ba za ta yanke ba a cikin al'ummar.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gabatar da ambaton umarni da kyakkyawan aiki da hana mummunan aiki, saboda dalilai kamar haka:
- Domin nuna falalar umarni da kyakkyawan aiki da hani da mummunan aiki.

• Kasancewar ana magana ne a kan fifita wannan al’umma a kan dukkan al’ummomi, muminansu da kafiransu, shi ya sa aka ambaci sifar da kowa ya yarda mai kyau ce.

• Kuma domin kasancewar umarni da kyakkyawan aiki da hani da mummuna yana matsayin garkuwa mai kare imani, sai aka fara faɗar sa da farko, domin makarin kowane abu ana gabatar da shi ne.

• Hakanan akwai shaguɓe ga Ma’abota Littafi waɗanda suke da’awar sun yi imani, amma sun kasa tsayawa su yi umarni da kyakkyawan aiki su yi hani da mummuna.

• Kuma don a nuna cewa wannan al’umma sun tsaya a kan wannan aiki ne saboda sun yi imani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da bayyana addininsa a fili.

Suratu Ali-Imran (110-112)

كُنتُمْ خَيْرَ أُمَّةٍ أُخْرِجَتْ لِلنَّاسِ تَأْمُرُونَ بِٱلْمَعْرُوفِ وَتَنْهَوْنَ عَنِ ٱلْمُنكَرِ وَتُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ ۗ وَلَوْ ءَامَنَ أَهْلُ ٱلْكِتَٰبِ لَكَانَ خَيْرًا لَّهُم ۚ مِّنْهُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ وَأَكْثَرُهُمُ ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿١١٠﴾ لَن يَضُرُّوكُمْ إِلَّآ أَذًى ۖ وَإِن يُقَٰتِلُوكُمْ يُوَلُّوكُمُ ٱلْأَدْبَارَ ثُمَّ لَا يُنصَرُونَ ﴿١١١﴾ ضُرِبَتْ عَلَيْهِمُ ٱلذِّلَّةُ أَيْنَ مَا ثُقِفُوٓا۟ إِلَّا بِحَبْلٍ مِّنَ ٱللَّهِ وَحَبْلٍ مِّنَ ٱلنَّاسِ وَبَآءُو بِغَضَبٍ مِّنَ ٱللَّهِ وَضُرِبَتْ عَلَيْهِمُ ٱلْمَسْكَنَةُ ۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقْتُلُونَ ٱلْأَنۢبِيَآءَ بِغَيْرِ حَقٍّ ۚ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَوا۟ وَّكَانُوا۟ يَعْتَدُونَ ﴿١١٢﴾

110. Ku ne mafi alherin al'umma waɗanda aka fitar ga mutane, kuna umarni da kyakkyawan aiki, kuma kuna hana mummuna, kuma kuna yin imani da Allah. Da a ce kuwa Ma’abota Littafi za su yi imani da ya fi alheri a gare su. A cikinsu akwai muminai, amma mafiya yawansu fasiƙai ne.

111. Ba za su taɓa iya cutar da ku ba sai dai cutarwa kaɗan; kuma in da za su yaƙe ku, sai sun juya muku baya, sannan ba za a taimake su ba.

112. An haɗa su da ƙasƙanci a duk inda aka same su, sai dai waɗanda suke riƙe da wani alƙawari daga Allah ko wani alƙawari daga mutane, kuma sun dawo da wani fushi daga Allah, kuma an haɗa su da talauci. Hakan kuwa saboda sun kasance suna kafirce wa ayoyin Allah, kuma suna kashe annabawa ba tare da wani haƙƙi ba, hakan yana faruwa ne saboda saɓo da suka yi, kuma sun kasance suna ƙetare iyaka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana magana da waɗannan al’umma. Farkon waɗanda suka shiga cikin wannan kiran, su ne sahabban Annabi, domin su ne farkon waɗanda ayar ta yi magana da su. Wannan matsayi mai girma sun cancance shi ne saboda sun siffantu da yin umarni da kyakkyawan aiki da hani da mummuna da kuma imani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Wannan ne ya sanya suka tsere wa al’ummomin da suka gabace su.

Da a ce Yahudawa da Nasara sun yi imani da Annabi (ﷺ) da abin da ya zo da shi daga Ubangijinsa, to da ya fi musu alheri. Sai dai waɗanda suka yi imani a cikinsu ‘yan kaɗan ne, da dama daga cikinsu sun ci gaba ne da zama a kan kangare wa Allah da Manzonsa (ﷺ). Wannan shi zai hana su ƙaunaci muminai sai dai su yi ta gaba da su da ƙoƙarin cutar da su duk sanda suka sami dama. Amma dai duk yadda suka kai ga nuna musu ƙiyayya da ƙoƙarin cin zarafinsu, ba za su iya ba in banda cutarwa da fatar baki ba. Idan ma da faɗa zai haɗa su da muminai; to ba za su iya taɓuka komai ba sai dai su gudu, kuma ba za a taimaka musu ba, domin kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa su da ƙasƙanci da wulaƙanci a duk inda suke a bayan ƙasa, ba sa samun nutsuwa da kwanciyar hankali, sai da wani alƙawari daga Allah ko daga mutane. Sannan kuma sun cancanci fushin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma ga alamun talauci sun bayyana a tare da su. Irin wannan sakamakon ya faru da su ne saboda kafirce wa ayoyin Allah da suke yi, da kuma kashe annabawa ba tare da wani laifi ba, sai don zalunci kawai. Kuma abin da ya kai su ga wannan hali na kafirci da kisa, shi ne saɓon Allah da suke yi da ƙetare iyakokinsa da shari’arsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Bayan ya soki ƙungiyar Ma’abota Littafi masu kafirce wa Allah, da kashe annabawa ba da wani haƙƙi ba. To don kada wani ya zaci duka haka halayensu suke, sai Allah ya bayyana cewa, a cikinsu akwai na kirki, masu halaye da yake so. To haka ya wajaba a riƙa yin adalci, ko da kuwa da wanda ake saɓani da shi ne.

2. Muhimmancin yawan karatun Alƙur’ani cikin dare. Kuma sallar nafila ta dare ta fi ta rana, saboda mai salla a lokacin ya fi tara hankalinsa wuri guda, domin babu wani abu da zai ɗauki hankalinsa kamar da rana, kuma akwai kauce wa riya a cikinta, da sauran wasu abubuwa masu rushe ayyuka, ko su naƙasa su.

3. Muhimmancin umarni da kyakkyawan aiki, da hana mummuna. Saboda muminai bayan sun inganta kansu da imani, kuma suna ƙoƙarin inganta wasu ta hanyar umartar su da kyawawan ayyuka, da kuma hana su munana, wannan kuwa shi ne matuƙar kamala.

4. An gabatar da ambaton karatun Alƙur’ani a kan imani da Allah da ranar lahira, domin bai yiwuwa mutum ya yi imani da abu, sai bayan ya san shi, don haka idan sun karanta ayoyin Allah, sai su san mene ne ranar lahira, sannan su yi imani da ita.

Suratu Ali-Imran (113-115)

*لَيۡسُواْ سَوَآءٗۗ مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ أُمَّةٞ قَآئِمَةٞ يَتۡلُونَ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ ءَانَآءَ ٱلَّيۡلِ وَهُمۡ يَسۡجُدُونَ ١١٣ يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَيَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَيُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١١٤ وَمَا يَفۡعَلُواْ مِنۡ خَيۡرٖ فَلَن يُكۡفَرُوهُۗ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِٱلۡمُتَّقِينَ ١١٥

113. Ba dukansu ne suka zama ɗaya ba. Cikin Ma’abota Littafi akwai al'umma tsayayya, suna karanta Littafin Allah a cikin dare alhalin suna sujada.

114. Suna yin imani da Allah da ranar ƙarshe, kuma suna umarni da kyakkyawan aiki, kuma suna hana mummuna, kuma suna hanzari wajen ayyukan alheri, waɗannan kuwa suna cikin salihan bayi.

115. Kuma duk abin da suka aikata na alheri, to ba za a hana musu ladansa ba. Kuma Allah Yana sane da masu taƙawa.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci ƙungiyar fasiƙai daga Ma’abota Littafi, sai kuma a waɗannan ayoyi ya bayyana cewa, ba dukkansu suka taru suka zama ɗaya ba; a cikinsu akwai mutanen kirki, waɗanda Allah ya shirye su suka musulunta, suka riƙe gaskiya, suna kuma karanta littafin Allah a cikin sallolinsu na dare, kuma suna yin imani da Allah da ranar lahira. Kuma ba su tsaya ga gyara zukatansu su kaɗai ba; suna yin nasu ƙoƙarin su gyara wasu ta hanyar umartar su da kyawawan ayyuka da hana su aikata munana suna kuma gaggawa wajen aikata ayyukan alheri. Irin waɗannan mutane su ne mutanen kirki salihai, kuma duk wani aikin alheri da za su yi ba za a haramta musu ladansa ba a wajen Allah. Allah kuma ya san masu taƙawa, yana ganin ayyukansu, kuma zai yi musu kyakkyawan sakamako a lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sanin cikar ikon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ta yadda babu wata hanya da kafirai za su iya bi su kare kansu daga azabarsa, komai yawan dukiyarsu da ‘ya’yansu, domin ba za su tsinana musu komai ba a wajen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Gargaɗi a kan guje wa ruɗuwa da yawan dukiya ko ‘ya’ya. Domin wanda duk ya ruɗu da su; to ba zai saurari mai faɗa masa gaskiya ba, domin shi a ganinsa yawan dukiyar da aka ba shi ya ishe shi komai, don haka da wuya ya saurari gaskiya, ko ya nemi saninta.

3. Ran mutum a wajensa amana ce Allah ya danƙa a hannunsa, don haka tilas ne ya kula da wannan amanar, kada ya aikata wani abu da zai cutar da ran nasa; idan har ya yi haka; to ya zama azzalumi.

4. Allah Ta’ala ya kebance dukiya da ‘ya’ya da ambato, domin su ne suka fi amfani ga mutum fiye da komai. Da dukiyarsa zai iya fansar kansa, ko ya kare kansa daga tafka asara; ‘ya’ya kuma za su taimaka wa mahaifinsu, su ba shi kariya. To idan ya zamanto ɗan da mutum ya haifa ba zai iya tsinana masa komai ba, kuma dukiyar da yake da iko a kanta ba za ta yi masa wani amfani ba; to mene ne bayan su zai amfane shi, ya tsare shi daga kamun Ubangijinsa?

Suratu Ali-Imran (116-117)

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗاۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١١٦ مَثَلُ مَا يُنفِقُونَ فِي هَٰذِهِ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا كَمَثَلِ رِيحٖ فِيهَا صِرٌّ أَصَابَتۡ حَرۡثَ قَوۡمٖ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ فَأَهۡلَكَتۡهُۚ وَمَا ظَلَمَهُمُ ٱللَّهُ وَلَٰكِنۡ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ١١٧

116. Lalle waɗanda suka kafirta, dukiyoyinsu da ‘ya’yansu ba za su wadatar da su komai ba a wurin Allah; kuma waɗannan su ne ma’abota wuta; suna masu dawwama a cikinta.

117. Misalin abin da suke ciyarwa a wannan rayuwa ta duniya kamar misalin iska ce mai tsananin sanyi, wadda ta auka kan shukar waɗansu mutanen da suka zalunci kawunansu, sai ta lalata ta. Kuma Allah bai zalunce su ba, sai dai kawunansu suke zalunta.

Bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci siffofin waɗanda suka yi imani daga cikin kafirai, sai kuma a waɗancan ayoyi Allah ya bayyana siffofin kafirai da azabar da ya tanada musu a ranar Alƙiyama, domin a gane bambancin da ke tsakanin mumini da kafiri. Allah ya bayyana cewa yawan dukiya da `ya`ya da kafirai suke taƙama da shi a duniya, a wurin Allah ba zai wadatar da su komai ba, domin ba zai kare su daga azabar Allah ba; za a jefa su wutar Jahannama ne, su dawwama a cikinta har abada.
Kuma dukiyar da kafirai suke ta ɓatarwa a nan duniya, da nufin yaƙar gaskiya da masu kira zuwa gareta, za su kashe ta ne a banza, domin ba za su taɓa cin nasara ba. Domin misalin wannan ta’asar da suke yi ta yi kama ne da wanda ya yi shuka, yana fatan samun amfaninta, sai wata guguwa mai ƙarfi da sanyi ta taso ta halaka shukar gaba ɗaya, bai tsira da komai ba daga amfaninta, kamar yadda Allah ya bayyana a *Suratu Anfal*, aya ta 36. Kuma wannan sakamako da Allah ya yi wa kafirai bai zalunce su da komai ba, su ne suka zalunci kawunansu ta hanyar kafirci da fafutukar sai sun bice hasken Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nisantar miyagun abokan shawara yana daga cikin imani, shi ya sa aka fuskantar da wannan maganar ga muminai.

2. A nan an nuna ba kowa ne ya kamata ya zama abokin shawara ba. Idan an jarrabi mutum da mu'amala da maƙiyi; to ya kamata mu'amalarsa ta kasance sama-sama, kada ya saki jiki ya riƙa buɗa masa sirrinsa, ko da kuwa zai rantse masa cewa yana son sa.

3. Faɗar Allah Ta'ala: "Sun so duk wani abu da zai ƙuntata muku...." yana nuna cewa, maƙiyammu suna son ganin duk abin da zai jefa mu cikin wahala, ya same mu; suna son ganin sun rushe mana tattalin arziƙinmu da tsarin siyasarmu da zamantakewarmu, su kuma rusa mana addininmu, wanda samun haka shi ya fi komai muhimmamci a wurinsu.

4. Aiki da lura da amfani da hankali wajen la'akari da ayoyin Allah, shi ne hanyar samun ilimi da wayewa.

5. Duk sa'adda mutum ya zama mai zurfin hankali ne; to ya fi fahimtar ayoyin Allah.

6. Gargaɗi ga muminai a kan haɗarin shugabantar da Yahudawa da Nasara a kan wani al'amarinsu na jagoranci. Domin su mutane ne da ba za su taƙaita ba wajen aikata wa Musulmi mugunta duk sanda suka samu dama. Kuma duk wani abin baƙin ciki da zai sami muminai to su za su yi farin ciki da shi ne; duk kuma wani abu na farin ciki da zai sami muminai to su baƙin ciki za su yi da shi. To irin waɗannan ta yaya muminai za su danƙa ragamar shugabancinsu a hannunsu?
7. Maƙiyanmu ba za su gaji da shirya mana makirci da sharri ba; to maganin wannan kawai shi ne haƙuri da taƙawa. Mu yi haƙuri wajen aikata duk wani umarni da aka ba mu, da guje wa duk wani abu da aka hana mu. Duk wanda ya yi haƙuri ya ji tsoron Allah; to yana ƙarƙashin kulawar Ubangijinsa, babu makircin da zai cutar da shi.

8. A ƙarƙashin aya ta 120, malamai suka fitar da ƙa'ida game da maƙiyi, suka ce shi ne wanda yake farin ciki da abin da ya baƙanta maka, yake baƙin ciki da abin da ya faranta maka.

Suratu Ali-Imran (118-120)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ بِطَانَةً مِّن دُونِكُمْ لَا يَأْلُونَكُمْ خَبَالًا وَدُّواْ مَا عَنِتُّمْ قَدْ بَدَتِ ٱلْبَغْضَآءُ مِنْ أَفْوَٰهِهِمْ وَمَا تُخْفِى صُدُورُهُمْ
أَكْبَرُ ۚ قَدْ بَيَّنَّا لَكُمُ ٱلْـَٔايَـٰتِ ۖ إِن كُنتُمْ تَعْقِلُونَ ﴿١١٨﴾ هَـٰٓأَنتُمْ أُوْلَآءِ تُحِبُّونَهُمْ وَلَا يُحِبُّونَكُمْ وَتُؤْمِنُونَ بِٱلْكِتَـٰبِ كُلِّهِۦ وَإِذَا لَقُوكُمْ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا
وَإِذَا خَلَوْاْ عَضُّواْ عَلَيْكُمُ ٱلْأَنَامِلَ مِنَ ٱلْغَيْظِ ۚ قُلْ مُوتُواْ بِغَيْظِكُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿١١٩﴾ إِن تَمْسَسْكُمْ حَسَنَةٌ تَسُؤْهُمْ وَإِن
تُصِبْكُمْ سَيِّئَةٌ يَفْرَحُواْ بِهَا ۖ وَإِن تَصْبِرُواْ وَتَتَّقُواْ لَا يَضُرُّكُمْ كَيْدُهُمْ شَيْـًٔا ۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا يَعْمَلُونَ مُحِيطٌ ﴿١٢٠﴾

118. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi abokanan shawara waɗanda ba a cikinku suke ba, ba za su sassauta muku mugunta ba, sun yi burin duk abin da zai ƙuntata muku, haƙiƙa ƙiyayya ta bayyana daga bakunansu; amma abin da zukatansu suke ɓoyewa ya fi girma. Haƙiƙa Mun bayyana muku ayoyi; in kun kasance kuna hankalta.

119. Sai ga shi ku ɗinnan kuna son su, su kuwa ba sa son ku, kuma ku kuna yin imani da Littattafai gaba ɗayansu, kuma idan sun gamu da ku, sai su ce: "Mun yi imani." Idan kuma sun keɓanta, sai su riƙa cizon 'yan yatsu a kanku saboda baƙin ciki. Ka ce: "Sai dai ku mutu da baƙin cikinku." Lalle Allah Masanin abin da yake cikin ƙiraza ne.

120. Idan wani kyakkyawan abu ya same ku sai ya baƙanta musu rai, amma idan wani mummunan abu ya same ku, sai su riƙa farin ciki da shi; amma idan kuwa kuka yi haƙuri, kuma kuka yi taƙawa, makircinsu ba zai cutar da ku komai ba. Lalle Allah Yana kewaye da sanin abin da suke aikatawa.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gama bayani a kan halayen muminai da na kafirai, sai kuma a waɗannan ayoyi yake gargaɗin muminai da kada su ɗauki kafirai abokan shawararsu, watau su janyo su kusa da su, suna nuna musu asirinsu, su bar 'yan'uwansu muminai domin waɗannan kafiran bai kamata a amince musu ba; duk sa'adda suka sami wata dama ta cutar da muminai; to sai sun yi amfani da ita. Kullum kuma suna jiran su ga muminai sun faɗa cikin wata wahala su kuma su samu abin yi musu dariya. Saboda tsananin ƙiyayyarsu ga muminai, har ta kai ba za su iya ɓoye ƙiyayyar a zuciyarsu ba, sai su riƙa suɓutar baki suna fito da ita a fili, duk da haka kuma ƙiyayyar da ke cikin zukatansu ta fi girma fiye da wadda bakunansu suka furta har muminai suka ji. Allah ya bayyana ayoyinsa ga muminai a fili, kuma bayanin zai amfane su har idan sun saurare shi, sun kuma fahimce shi.

An karɓo daga Abu Sa'id Alkhudiri (Allah ya kara masa yarda) ya ce, Annabi (ﷺ) ya ce: "Babu wani annabi da Allah ya taɓa aiko shi, ko wani halifa da Allah ya ba shi halifanci, face yana da kashi biyu na masu ba shi shawara; kashin farko suna umartar sa da kyakkyawan aiki, suna kwaɗaitar da shi a kai; kashi na biyu kuwa suna umartarsa da sharri, kuma suna kwaɗaitar da shi a kan aikata shi. To tsararre shi ne wanda Allah ya tsare." [Bukhari #7198].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani abu da ya wajaba muminai su yi hattara da shi dangane da sha'anin kafirai da munafuƙai; wannan abu kuwa shi ne saboda tsananin ƙiyayya da hassadar da ke cikin zukatansu ga muminai, ba za su taɓa jin suna son su a zukatansu ba. Su muminai kam suna nuna suna ƙaunar su su kuma kafirai ba sa son su, ba sa kuma ƙaunar su; tsakaninsu da su ƙiyayya ce kawai. Kamar yadda muminai suka yi imani da duk littattafan da Allah ya saukar wa annabawa, amma su kafirai na Yahudu da Nasara sun ƙi yin imani da abin da aka saukar ga Annabi (ﷺ), bayan kuma sun jirkita nasu littattafan. To duk wanda irin wannan ne halinsa; to kamata ya yi a ƙi shi, ba a so shi ba. Ba a nan halinsu ya tsaya ba; yana daga cikin miyagun halayensu na munafirci, duk sa'adda za su haɗu da muminai sai su riƙa nuna musu sun yi imani, amma kuma da zarar sun ware, sun kaɗaita da junansu, sai su riƙa cizon 'yan yatsunsu, saboda tsananin baƙin ciki da haushin muminai, domin suna ganin irin haɗin kan muminai da ƙaunar da ke tsakaninsu. Sai Allah ya umarci Annabinsa (ﷺ) ya gaya musu: "Sai dai ku mutu da baƙin cikinku," domin Allah ya yi alƙawarin sai ya cika wannan ni'imar tasa, ya ɗaukaka addininsa ko ba sa so, sai dai baƙin ciki ya kashe su. Allah kuma yana sane da abin da yake ɓoye a cikin ƙirazan bayinsa, don haka zai yi wa kowa sakayya a kan abin da ya aikata.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da yake ƙara tsananin gabar kafiran ga muminai, watau duk lokacin da wani abin farin ciki ya sami muminai, sai su riƙa jin haushi, suna damuwa; yayin da kuma wani abin baƙin ciki ya same su, sai su riƙa murna, suna jin daɗi. Sai Allah ya koyar da muminai abin da zai taimaka musu wajen jure irin wannan hali na kafirai, watau su zama masu haƙuri, kuma masu taƙawa, domin idan har sun rungumi waɗannan siffofi guda biyu, to babu wani makirci da zai cutar da su. Allah yana kewaye da saninsa game da abin da waɗannan kafiran da munafuƙan suke yi, kuma zai saka musu a kan hakan.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwarewar Annabi (ﷺ) wajen tsara sojojinsa a wurin yaƙi.

2. Abu ne mai matuƙar muhimmanci ga jagoran mayaƙa, ya shirya mayaƙansa, kowanne ya nuna masa wurin tsayuwarsa da ya dace da shi, domin yin hakan yana ɗaya daga cikin sabubban samun nasara a yaƙi.

3. Kariya daga Allah take. Ba don wannan kariyar ba, da babu wanda zai kuɓuta daga aukawa cikin ramukan saɓon Allah da zunubbai.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai rufa asirin bayinsa ne masu laifi. Don haka a nan sai Allah bai faɗi sunan ƙabilun da suka yi nufin janyewa daga fagen yaƙi tare da Annabi ba, kawai sai ya ce 'waɗansu ƙungiyoyi biyu'.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai tausaya wa bawansa ne, sai ya nufe shi da tsayawa da jajircewa a kan gaskiya.

6. Wajabcin dogara ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka); yin haka yana daga cikin imani da Allah.

7. Ya wajaba ga Musulmi ya sama wa kansa kariya daga duk wani abin ƙi, ta hanyar dogaro ga Allah, ka da ya zama mai raki.

8. Taƙawa tana daga cikin hanyoyin gode wa Allah; ita ce Musulmi zai sanya ta zama katanga tsakaninsa da azabar Allah, watau dai ya aikata abin da aka wajabta masa, ya kuma bar abin da aka haramta masa. Wannan kuwa shi ne haƙiƙanin godiya ga Allah.
9. Duk sa'adda bawa ya fi nuna ƙasƙancinsa ga Allah; to ya fi kusa da samun nasararsa. A duk kuma lokacin da bawa yake nuna isarsa; to lokacin ne yake rasa samun taimakon Allah a gare shi.

10. Bayanin irin kyakkyawar mu'amalar Manzon Allah (ﷺ) ga sahabbansa lokacin da suke fuskantar wata fargaba da tashin hankali. Annabi (ﷺ) yakan shigar musu da kyakkyawan fata a zukatansu, wanda hakan shi ne yakan dawo musu da kuzarinsu, ya tafiyar musu da baƙin cikinsu da damuwarsu, ya sa su tashi tsaye domin aiki ba ja da baya.

11. Sama ita ce mazaunin mala'iku, sai dai sau tari sukan sauko ƙasa da umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

12. Allah yakan ba wa muminai nasara a kan kafirai, domin ya rage mugun iri, ba don ya halaka duk ilahirin kafirai ba. Saboda yana daga cikin hikimar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya bar imani da kafirci su ci gaba da wanzuwa, suna ta ƙaruwa, domin tantance mumini na gaskiya da wanda ba na gaskiya ba.

13. Cewar da Allah ya yi, al'amari ba a hannun Annabi (ﷺ) yake ba, yana nuna al'amarin halittun Ubangiji ba mallakinsa ne ba, don haka ba ya halatta mumini ya roƙe shi, ko ya nemi agajinsa da taimakonsa a kan abin da ba mai yin sa sai Allah, ballantana kuma wani waliyyi.

14. Annabi (ﷺ) shi ma bawa ne na Allah, kuma har ya bar duniya yana karɓar umarni da hani ne daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Da wannan ne za mu fahinci ɓatan masu da'awar cewa, akwai wasu waliyyai da suke kaiwa matakin da sun fi ƙarfin su karɓi umarni ko hani daga Allah, ko kuma bawa ya kai wani matakin da shari'a take sauka daga kansa. Wannan kafirci ne, ba Musulunci ba.

15. Allah yakan yi wa kafirai azabar da babu hannun wani Musulmi a ciki.

Suratu Ali-Imran (121-129)

وَإِذۡ غَدَوۡتَ مِنۡ أَهۡلِكَ تُبَوِّئُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ مَقَٰعِدَ لِلۡقِتَالِۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ١٢١ إِذۡ هَمَّت طَّآئِفَتَانِ مِنكُمۡ أَن تَفۡشَلَا وَٱللَّهُ وَلِيُّهُمَاۗ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١٢٢ وَلَقَدۡ نَصَرَكُمُ ٱللَّهُ بِبَدۡرٖ وَأَنتُمۡ أَذِلَّةٞۖ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٢٣ إِذۡ تَقُولُ لِلۡمُؤۡمِنِينَ أَلَن يَكۡفِيَكُمۡ أَن يُمِدَّكُمۡ رَبُّكُم بِثَلَٰثَةِ ءَالَٰفٖ مِّنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ مُنزَلِينَ ١٢٤ بَلَىٰٓۚ إِن تَصۡبِرُواْ وَتَتَّقُواْ وَيَأۡتُوكُم مِّن فَوۡرِهِمۡ هَٰذَا يُمۡدِدۡكُمۡ رَبُّكُم بِخَمۡسَةِ ءَالَٰفٖ مِّنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ مُسَوِّمِينَ ١٢٥ وَمَا جَعَلَهُ ٱللَّهُ إِلَّا بُشۡرَىٰ لَكُمۡ وَلِتَطۡمَئِنَّ قُلُوبُكُم بِهِۦۚ وَمَا ٱلنَّصۡرُ إِلَّا مِنۡ عِندِ ٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَكِيمِ ١٢٦ لِيَقۡطَعَ طَرَفٗا مِّنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَوۡ يَكۡبِتَهُمۡ فَيَنقَلِبُواْ خَآئِبِينَ ١٢٧ لَيۡسَ لَكَ مِنَ ٱلۡأَمۡرِ شَيۡءٌ أَوۡ يَتُوبَ عَلَيۡهِمۡ أَوۡ يُعَذِّبَهُمۡ فَإِنَّهُمۡ ظَٰلِمُونَ ١٢٨ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ يَغۡفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٢٩ وَإِذۡ غَدَوۡتَ مِنۡ أَهۡلِكَ تُبَوِّئُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ مَقَٰعِدَ لِلۡقِتَالِۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ١٢١ إِذۡ هَمَّت طَّآئِفَتَانِ مِنكُمۡ أَن تَفۡشَلَا وَٱللَّهُ وَلِيُّهُمَاۗ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١٢٢ وَلَقَدۡ نَصَرَكُمُ ٱللَّهُ بِبَدۡرٖ وَأَنتُمۡ أَذِلَّةٞۖ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٢٣ إِذۡ تَقُولُ لِلۡمُؤۡمِنِينَ أَلَن يَكۡفِيَكُمۡ أَن يُمِدَّكُمۡ رَبُّكُم بِثَلَٰثَةِ ءَالَٰفٖ مِّنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ مُنزَلِينَ ١٢٤ بَلَىٰٓۚ إِن تَصۡبِرُواْ وَتَتَّقُواْ وَيَأۡتُوكُم مِّن فَوۡرِهِمۡ هَٰذَا يُمۡدِدۡكُمۡ رَبُّكُم بِخَمۡسَةِ ءَالَٰفٖ مِّنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ مُسَوِّمِينَ ١٢٥ وَمَا جَعَلَهُ ٱللَّهُ إِلَّا بُشۡرَىٰ لَكُمۡ وَلِتَطۡمَئِنَّ قُلُوبُكُم بِهِۦۚ وَمَا ٱلنَّصۡرُ إِلَّا مِنۡ عِندِ ٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَكِيمِ ١٢٦ لِيَقۡطَعَ طَرَفٗا مِّنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَوۡ يَكۡبِتَهُمۡ فَيَنقَلِبُواْ خَآئِبِينَ ١٢٧ لَيۡسَ لَكَ مِنَ ٱلۡأَمۡرِ شَيۡءٌ أَوۡ يَتُوبَ عَلَيۡهِمۡ أَوۡ يُعَذِّبَهُمۡ فَإِنَّهُمۡ ظَٰلِمُونَ ١٢٨ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ يَغۡفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٢٩

121. Kuma ka tuna lokacin da ka yi sammako daga wajen iyalinka, ka je kana shirya wa muminai wuraren tsayuwarsu don yaki. Allah kuwa Mai ji ne, Masani.

122. Tuna lokacin da wadansu kungiyoyi guda biyu daga cikinku suka yi niyyar su ja da baya, amma Allah ne Majibincin lamarinsu. Sai muminai su dogara ga Allah kadai.

123. Kuma tabbas hakika Allah Ya taimake ku a (yakin) Badar, alhalin kuna raunana, to ku ji tsoron Allah don ku zamanto masu godiya a gare Shi.

124. Ka tuna lokacin da kake ce wa muminai: “Shin bai ishe ku ba idan Ubangijinku Ya kawo muku agajin mala’iku dubu uku wadanda za a saukar da su (daga sama)?”

125. Haka ne, idan har za ku yi hakuri, kuma ku yi takawa, kuma (kafirai) suka auko muku cikin gaggawa a wannan lokacin, to Ubangijinku zai karo muku agaji da mala’iku dubu biyar masu alamomi.

126. Kuma Allah bai sanya wannan ba sai don albishir a gare ku, kuma domin zukatanku su nutsu da shi. Kuma nasara ba ta zuwa daga kowa sai daga Allah Mabuwayi, Mai hikima.

127. Domin Ya karya lagon wani bangare na kafirai ko Ya kaskantar da su, sai su juya da baya suna tababbu.

128. Ba ka da komai cikin lamarin, ko dai (Allah) Ya karbi tubansu, ko Ya yi musu azaba, lalle su dai azzalumai ne.

129. Kuma abin da yake cikin sammai da kuma abin da yake cikin kasa na Allah ne. Yana yin gafara ga wanda Ya ga dama, Yana kuma yin azaba ga wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mai gafara ne, Mai jin kai.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, haƙuri da taƙawa su ne makamin da mumini zai tsare kansa da shi daga cutarwar maƙiyansa, sai kuma a waɗannan ayoyi Allah ya fito da bayanin abubuwan da kan sabbaba rashin samun nasara a kan maƙiya.
Allah yana tunatar da Annabinsa Muhammadu (ﷺ) lokacin da ya fito daga gidansa domin haɗuwa da kafiran Makka a ranar yaƙin Uhudu, lokacin da yake shirya rundunar muminai domin fita yaƙi, yana sanya kowa a muhallin da ya dace da shi. Domin Allah yana jin komai, yana jin shawarar da Annabi (ﷺ) ya yi da sahabbansa a kan wurin da ya kamata a yi wannan yaƙi. Kuma Allah shi ne masani dangane da ra'ayin da ya fi dacewa daga cikin ra'ayoyin da aka kawo a lokacin. Kuma yana sane da irin mugun nufin da kafirai da munafuƙai suka ɓoye a zukatansu, har ma da abin da daukacin halittunsa suka ɓoye a zukatansu.
Allah yana tunatar da Annabi (ﷺ) lokacin da wasu ƙungiyoyi biyu daga cikin muminai, suka yi nufin su janye daga wannan yaƙi, su ne ƙabilun Banu Salima da na Banu Harisa, sai dai kuma Allah ya kafe dugadugansu. Allah ya sanar wa Annabi (ﷺ) cewa, gare shi shi kaɗai ya wajaba muminai su dogara.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya kara masa yarda) ya ce: A kanmu wannan ayar ta sauka: "Ka tuna lokacin da wasu ƙungiyoyi biyu daga cikinku suka yi nufin su ja da baya, amma Allah ne majiɓincin lamarinsu…" Jabir ya ce: Mu ne ƙungiyoyin biyu, watau ƙabilar Banu Harisa da ƙabilar Banu Salima, kuma saukar da wannan ayar ya faranta mini rai, saboda faɗarsa (Mai tsarki da ɗaukaka): "...amma Allah ne majiɓincin lamarinsu…" [Bukhari #4558].
Allah yana goranta wa muminai nasarar da ya ba su a ranar yaƙin Badar ne a yayin da suke 'yan kaɗan, masu rauni. Don haka ya dace su ji tsoron sa, su kiyaye dokokinsa, don su gode masa da baiwar da ya yi musu.
Sannan ya sake tunatar da Annabinsa Muhammad (ﷺ), lokacin da yake yi wa sahabbansa albishir, yana cewa: "Shin ba zai ishe ku ba, Allah ya kawo muku ɗauki na mala'iku dubu uku, waɗanda zai sauko da su daga sama su taya ku yaƙi?" To hakanan zai kawo muku tallafi na mala'iku dubu biyar, waɗanda suke da alamar jarunta tare da su, idan har kun yi haƙuri, kuma kun yi taƙawa, kuma mushirikai sun ɓullo muku ta inda suka ɓullo cikin gaggawa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, sanar da su da ya yi cewa, zai kawo musu agaji na mala'iku, wani albishir ne yake yi musu, domin su sami nutsuwar zukata. Daga ƙarshe, nasara daga Allah take shi kaɗai, shi ne Mabuwayi, wanda ya fi ƙarfin kowa, kuma mai hikima, zai ba su nasara ya kuma halakar da wasu kafiran, ko ya tozartar da wasu daga cikinsu, ya wulaƙanta su, daga ƙarshe su koma garuruwansu a wulaƙance, ba tare da sun cim ma wata nasara ba. Ko kuma idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ga dama ya shiryar da su su musulunta, ko kuma ya yi musu azaba saboda zaluncinsu. Duk dai al'amuransu gaba ɗaya suna komawa ne ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), babu komai na al'amarinsu da yake a hannun wannan Annabi (ﷺ).

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya kara masa yarda) ya ce: An karya wa Annabi (ﷺ) haƙorinsa na gaba ranar yaƙin Uhudu, aka kuma fasa masa kai, sai ya riƙa share jini daga jikinsa yana cewa: "Ta yaya mutanen da suka fasa kan Annabinsu, suka karya masa haƙorinsa na gaba za su rabauta, alhalin yana kiran su zuwa ga Allah?" Sai Allah Ta'ala ya saukar da faɗarsa: "Babu wani al'amari da yake hannunka...." [Muslim #1791].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, shi kaɗai ne mai mulkin duk wani abu da yake sama, da wanda yake ƙasa, yana kuma yafe wa wanda ya ga damar yafe masa daga cikin bayinsa, ya kuma yi uƙuba ga wanda ya ga damar yi masa uƙuba, amma duk da haka shi mai yawan gafara ne, mai yawan rahama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kaurace wa cin riba yana daga cikin imani.

2. Taƙawa ita take sa bawa ya guje wa aikata abin da ya saba aikatawa wanda Allah ba ya so.

3. Bawa yana sa ran samun rahamar Allah ne yayin da ya yi biyayya ga Allah da Manzonsa (ﷺ).

4. Dalilin ambaton ‘ninkin-ba-ninkin’ a lamarin riba, saboda abin da yake faruwa ke nan a lokacin da ayar take sauka. Domin mutum a lokacin yakan ba wa wani bashi amma da ƙari, shi kuma sai ya biya shi a lokacin da suka ƙayyade a tsakaninsu. Idan lokacin biya ya yi ba shi da abin da zai biya, sai mai kuɗin ya ƙara masa lokaci, tare da ƙara masa wani kuɗin na riba a kan na da, da haka, da haka har ribar ta ninninka uwar kuɗin. Shi ne ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin abin da yake faruwa, ba wai ana nufin riba ba za ta zama haramun ba sai ta zama ninkin-ba-ninkin, kamar yadda wasu suke da’awa. Riba haramun ce komai ƙarancinta, kamar yadda Allah ya bayyana a *Suratul Baƙara*, aya ta 278.

5. Bayanin an riga an halicci wutar Jahannama, tana nan an tanade ta domin kafirai masu dawwama a cikinta har abada. Amma Musulmai masu sabon Allah, su za su shige ta ne a yi musu azaba gwargwadon laifuffukansu, sannan a fitar da su daga cikinta.

Suratu Ali-Imran (130-132)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَأۡكُلُواْ ٱلرِّبَوٰٓاْ أَضۡعَٰفٗا مُّضَٰعَفَةٗۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ١٣٠ وَٱتَّقُواْ ٱلنَّارَ ٱلَّتِيٓ أُعِدَّتۡ لِلۡكَٰفِرِينَ ١٣١ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ١٣٢

130. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ci riba ninki-ba-ninkin, kuma ku kiyaye dokokin Allah don ku rabauta.

131. Kuma ku kiyayi wuta wadda aka riga aka yi tanadinta domin kafirai.

132. Kuma ku bi Allah da Manzo don a ji ƙan ku (a ranar tashin alƙiyama).

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya taimaka wa muminai yayin da suke raunana, kuma ya taimake su ne saboda taƙawarsu da bin umarninsa; haka kuma lokacin da suka sami matsala a yaƙin Uhudu saboda saba wa umarnin Manzon Allah (ﷺ) da suka yi, sai kuma a nan Allah ya tsawace su da su guji tsananin kwaɗayin tara dukiya, musamman ta hanyar cin dukiyar riba ninkin-ba-ninkin, wanda yana daga manyan laifukan da suka yaɗu a wannan lokacin. Sannan kuma ya nuna musu hanyar samun taƙawa, wadda ita ce tafarkin samun duk wata nasara. Taƙawa da ma ita ce aikata umarnin Allah da guje wa haninsa. Don haka a ƙarshen waɗannan ayoyi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin muminai da su ji tsoron Allah, don su sami rabauta duniya da lahira, kuma su kiyayi wuta, ta hanyar sanya shamaki tsakaninsu da ita, wadda an shirya ta ne musamman domin kafirai, waɗanda suka bijire wa imani da Allah da abin da ya saukar wa Annabinsa (ﷺ). Ya umarci muminai da su yi wa Allah ɗa’a da Manzonsa, domin da haka ne za su sami rahama duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a kan gaggawar yin ayyukan samun gafara daga Allah da shiga Aljanna.

2. Ciyar da dukiya don Allah yana daga cikin manyan ayyukan da suke kai bawa gidan Aljanna.

3. Haɗiye fushi da haƙura a kan ɗaukar matakin ramuwa, duk kuwa da samun ikon yin hakan, yana daga cikin manya-manyan kyawawan halaye, sannan kuma babbar ibada ce.

4. Kwaɗaitarwa a kan yin afuwa ga mutane idan suka yi ba daidai ba, yayin da suka gyara, kuma suka nemi afuwa.

5. Kwaɗaitarwa a kan kyautata wa mutane, kuma Allah yana son masu kyautata wa wasu.

6. Kwaɗaitarwa a kan yawan istigfari da yin tuba na gaskiya, tare da nadama a kan zunubin da ya gabata da kuma niyyar ba zai sake komawa ba.

7. Babu wanda zai iya gafarta wa wani zunubbansa sai Allah shi kaɗai. Don haka ba a neman gafara a wurin wani ba Allah ba.

8. Komawa ga aikata laifi ba ya hana a sake yin tuba. Abin da ba a so shi ne mai laifi ya doge a kan laifinsa yana sane.
9. Mai taƙawa ba ana nufin wanda ba ya saba wa Allah ba ne; a'a, ana nufin wanda kyawawan ayyukansa suka fi munana, sannan ba ya kafewa a kan aikata laifi, kuma yana gaggauta neman gafara da tuba ga Allah, duk sa'adda ya aikata laifi.

Suratu Ali-Imran (133-136)

*وَسَارِعُوٓاْ إِلَىٰ مَغۡفِرَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ وَجَنَّةٍ عَرۡضُهَا ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلۡأَرۡضُ أُعِدَّتۡ لِلۡمُتَّقِينَ ١٣٣ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ فِي ٱلسَّرَّآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَٱلۡكَٰظِمِينَ ٱلۡغَيۡظَ وَٱلۡعَافِينَ عَنِ ٱلنَّاسِۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٣٤ وَٱلَّذِينَ إِذَا فَعَلُواْ فَٰحِشَةً أَوۡ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ ذَكَرُواْ ٱللَّهَ فَٱسۡتَغۡفَرُواْ لِذُنُوبِهِمۡ وَمَن يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ وَلَمۡ يُصِرُّواْ عَلَىٰ مَا فَعَلُواْ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٣٥ أُوْلَٰٓئِكَ جَزَآؤُهُم مَّغۡفِرَةٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَجَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَنِعۡمَ أَجۡرُ ٱلۡعَٰمِلِينَ ١٣٦

133. Kuma ku yi gaggawa zuwa ga neman gafara ta musamman daga wajen Ubangijinku, da kuma Aljanna wadda faɗinta yake daidai da sammai da ƙasa, an yi tanadinta domin masu taƙawa.

134. Su ne waɗanda suke ciyarwa a cikin halin yalwa da halin ƙunci, kuma masu ɓoye fushi kuma masu yin afuwa ga mutane. Allah kuwa Yana son masu kyautatawa.

135. Su ne kuma waɗanda idan sun aikata mummunan aiki, ko suka zalunci kansu, nan take sai su tuna da Allah, sai su nemi gafarar zunubansu. Wane ne kuwa mai gafarta zunubbai in ba Allah ba? Kuma ba sa zarcewa a kan abin da suka yi, alhali suna sane.

136. Waɗannan sakamakonsu shi ne gafara ta musamman daga Ubangijinsu, da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu. Kuma madalla da sakamakon masu aiki.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da yin gaggawa wajen samun gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), da samun shiga Aljanna, wadda faɗinta ya kai girman sammai da

ƙassai. An tanade ta domin masu taƙawa, su ne masu ba da dukiyarsu taimako a halin suna cikin yalwa ko halin ƙunci, ba sa rowar abin da suka mallaka. Kuma suna iya mallakar zukatansu lokacin fushi, suna danne ɓacin ransu, kuma masu afuwa ga waɗanda suka munana musu. Waɗannan siffofi ne na masu kyautatawa, Allah kuwa yana son masu kyautatawa.
Har wa yau, yana daga cikin siffofin muminai idan sun aikata wani laifi, ko saɓo sai su tuna Allah, su nemi gafararsa domin babu mai gafarta zunuban bawa, sai Allah shi kaɗai, kuma ba sa ci gaba da aikata wannann laifin alhalin suna sane da cewa Allah zai yi musu uƙuba, kuma suna sane da cewa, tuba wajibi ne a kan duk wanda ya saɓa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma Allah yana karɓar tuban wanda ya tuba. Masu waɗannan siffofi suna da wata gafara daga Allah, kuma za su shiga gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu; masaukansu ke nan na har abada. Madalla da sakamakon masu aiki.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a kan yin izina da wa'azi daga abubuwan da suka faru ga al'ummomin da suka gabata.

2. Nuni a kan cewa abin da ya faru ga masu ƙaryatawa na farko, irinsa zai iya faruwa ga masu ƙaryatawa na yau da na gobe. Don haka al'umma su kwantar da hankulansu a kan duk wani zalunci da yake faruwa gare su, kuma su yi taka-tsan-tsan kada su shigar da kansu cikin masu ƙaryatawa, sai uƙubar da ta same su su ma ta haɗa da su. Don haka a nan akwai lallashi, da kuma jan kunne.

3. Allah yana kwantar da hankalin Musulmi cewa, gwagwarmaya tsakanin gaskiya da ƙarya wani daɗaɗɗen abu ne a tarihin kafuwar duniya, kuma koyaushe masu gaskiya ne suke samun galaba a kan maƙaryata ta hanyar taƙawa da haƙuri.

4. Ana yin tafiya ne a bayan ƙasa don wata kyakkyawar manufa a shari'ance. Amma idan tafiye-tafiyen mutum ba da wata kyakkyawar manufa ba ne, to wannan wahalar da kai ne kawai da ɓarnar dukiya wadda shari'a ta hana.

5. Alƙur'ani littafi ne da ya zo da shiriya ga mumini da kafiri.

6. Alƙur'ani ya tattara bayanai a kan kowane abu kuma ga kowa da kowa, babu abin da Allah bai aje tushen bayaninsa a Alƙur'ani ba, hakanan babu wanda bayanin Alƙur'ani bai shafe shi ba.

7. Babu masu amfanuwa da Alƙur'ani sai masu taƙawa. Don haka taƙawa ita ce musabbabin samun shiriyar Allah, da kuma wa'azantuwa da Alƙur'ani.

8. Wanda duk bai wa'azantu da Alƙur'ani ba, to ya tuhumi kansa.

9. Duk sa'adda taƙawar mutum ta ƙaru, to shiriyarsa da wa'azantuwarsa da Alƙur'ani ma za su ƙaru.

10. Imani yana ƙara sanya wa zuciya ƙarfi da ƙarin dogaro ga Allah a cikinta.

11. Ya kamata mumini a kullum ya kasance mai ƙarfin hali da rashin karayar zuci, domin duk sa'adda mutum ya karaya, ya yi rauni, to zai yi asarar alheri mai yawa. Da zarar ya tashi tsaye da ƙarfinsa, to zai cim ma samun duk alhairin da yake nema da izinin Allah, domin ba wanda ya san gobe sai Allah.

12. Duk sa’adda imanin al’umma ya ƙaru, to ɗaukakarta ma za ta ƙaru, don haka bawa yana samun ɗaukaka ne a wurin Allah, gwargwadon imaninsa.

13. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan haɗa bawansa da nau’in jarraba iri-iri don ya gwada imaninsa.

14. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya rayuwar duniya ta zama mai jujjuyawa ga ɗan’adam daga daɗi zuwa wuya, daga wuya zuwa daɗi ko daga sharri zuwa alheri ko daga alheri zuwa sharri, domin kada mutum ya nutsu a kan cewa kullum zai yi ta zama ne a yanayin
jin daɗi, wanda hakan yana iya mantar da shi ranar lahira. Kuma da a ce Allah ya aje duniya a yanayin azaba koyaushe, to da ɗan’adam ya jikkata.

15. A cikin waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi zukatan muminai a kan matsalar da ta same su a yaƙin Uhudu sai ya bayyana musu wasu hikimomin da suka sa ya yi hakan, kamar haka:
• Ita duniya Allah yana bayar da ita ga mumini da kafiri, saboda da man ita gida ne mai ƙarewa, saɓanin lahira, ita Allah ba ya bayar da ita sai ga mumini kaɗai.
• Allah yana jarrabar bayinsa ya sa kafirai su yi galaba a kansu don tantance tsakanin mumini na gaskiya da wanda ba na gaskiya ba.
• Da a ce koyaushe Musulmi su ne masu cin nasara a kan kafirai, to da sai mutane su riƙa shiga Musulunci ba don suna so ba, sai don suna tsoro.
• Allah yakan ɗora kafirai a kan Musulmi, a wasu lokuta su kashe su, domin ya zaɓi shahidai a cikinsu.
• Don Allah ya tsarkake muminai daga zunubbansu.
• Don Allah ya halaka kafirai da azabarsa yayin da kafircinsu da zaluncinsu suka tsananta.

16. Faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cewa: “Allah ba ya son azzalumai.” yana nuna cewa, shahidai ba sa yin zalunci ta hanyar saɓa wa Allah da Manzonsa cikin ayyukansu. Don haka wanda ya mutu ta hanyar zaluntar wasu ba zai taɓa zama shahidi ba a wurin Allah, don Allah ba ya son azzalumai.

17. Duk sa’adda aka siffanta wata daula da siffar zalunci, to ba za ta yi ƙarko ba, Allah zai kawar da ita komai daɗewa.

Suratu Ali-Imran (137-141)

قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِكُمْ سُنَنٌ فَسِيرُواْ فِي ٱلْأَرْضِ فَٱنظُرُواْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُكَذِّبِينَ ﴿١٣٧﴾ هَٰذَا بَيَانٌ لِّلنَّاسِ وَهُدًى وَمَوْعِظَةٌ لِّلْمُتَّقِينَ ﴿١٣٨﴾
وَلَا تَهِنُواْ وَلَا تَحْزَنُواْ وَأَنتُمُ ٱلْأَعْلَوْنَ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٣٩﴾ إِن يَمْسَسْكُمْ قَرْحٌ فَقَدْ مَسَّ ٱلْقَوْمَ قَرْحٌ مِّثْلُهُۥ ۚ وَتِلْكَ ٱلْأَيَّامُ نُدَاوِلُهَا بَيْنَ
ٱلنَّاسِ وَلِيَعْلَمَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَيَتَّخِذَ مِنكُمْ شُهَدَآءَ ۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٤٠﴾ وَلِيُمَحِّصَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَيَمْحَقَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿١٤١﴾

137. Haƙiƙa sunnoni (na Allah) sun riga sun shuɗe gabaninku, to sai ku yi tafiya cikin ƙasa, sai ku duba ku ga yaya ƙarshen masu ƙaryatawa ya zama?

138. Wannan bayani ne don mutane, kuma shiriya ce da kuma wa’azi ga masu taƙawa.

139. Kuma kada ku yi rauni, kada kuma ku yi baƙin ciki, kuma ku ne mafiya ɗaukaka in dai har kun kasance muminai.

140. Idan ma wani miki ne ya same ku a jiki, to haƙiƙa miki irinsa ya sami mutanen (Makka). Kuma waɗannan kwanaki ne da muke jujjuya su tsakanin mutane domin Allah Ya bayyanar da waɗanda suka yi imani (a gane su), kuma Ya riƙi shahidai a cikinku. Allah kuwa ba Ya son azzalumai.

141. Kuma don Allah Ya tace waɗanda suka yi imani, kuma don Ya halakar da kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana lallashin zukatan Musulmi ne bayan abin da ya faru gare su a yaƙin Uhudu, na kashe da dama daga cikinsu da kafirai suka yi. Allah yana bayyana musu cewa, su zagaya a bayan ƙasa don su ga yadda sunnonin Allah suka faru ga al'ummomin da suka gabace su, su ga yadda Allah ya yi wa kafiran farko. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma yana nusar da su cewa, shi Alƙur'ani bayani ne ga ɗaukacin mutane, yana fayyace musu gaskiya, yana kuma nuna musu hanyar ɓarna don su guje ta, sannan yana shiryar da masu taƙawa zuwa miƙaƙƙiyar hanya, yana gargaɗin su da nisantar hanyoyin ɓata.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya umarci Musulmi da kada su yi rauni domin abin da ya same su a yaƙin Uhudu; su ne ko yaushe suke a sama, kuma masu rinjaye matuƙar suna riƙe da imaninsu. Idan suna ganin an kashe musu 'yan'uwa a yaƙin Uhudu ko an yi wa wasu raununnika, to su tuna su ma kafiran irin haka ya faru gare su, an kashe wasu da dama daga cikinsu, an raunana wasu a yaƙin Uhudu da yaƙin Badar. Don haka kada su ci gaba da wannan ɗamuwar da suke ciki, su sani wannan sunna ce ta Allah, haka yake jujjuya kwanaki a tsakanin mutane, yau ku yi nasara, gobe kuma maƙiyanku su yi nasara a kanku. To amma hikimar Allah a irin wannan aiki nasa ita ce don ya rarrabe tsakanin muminai na gaskiya da waɗanda suke na jabu, kuma Allah ya nufi wasu muminai da yin shahada, watau waɗanda za a kashe don ɗaukaka addininsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya son azzalumai, waɗanda su ne kafirai da munafuƙai fanɗararru waɗanda suka zalunci kawunansu. Kuma yana daga hikimar Allah a wannan aiki nasa, ya tsarkake muminai daga zunubbansu a dalilin abin da ya same su na kisa da raunatarwa, domin idan ya zamanto koyaushe su suke ta samun nasara, to sai ji-ji-da-kai ya shiga zukatansu, sai kuma su sami raunin imani, wanda kuma shi ne zai jawo musu fushin Allah da azabarsa. Sannan kuma Allah ya yi alƙawarin sai ya halakar da kafirai saboda ɗagawarsu da zurfafawa cikin zalunci da kafirci, wanda shi zai sa Allah ya kawar da su daga bayan ƙasa gaba ɗayansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Son Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da son gidan lahira ba kawai da fatar baki yake ba; abu ne da yake tare da aiki da jarrabawa ta Ubangiji. Yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai jarraba bayinsa da wata masifa to a nan ne zai tantance mumini na gaskiya da bara-gurbi.

2. Ba a shiga Aljanna ta hanyar buri kaɗai; ana samun Aljanna ne ta hanyar aiki nagari da juriya a kan barin saɓa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Bai dace ga mumini ya riƙa yi wa kansa fatan gamuwa da mummunan abu ko mai wahala ba. Don haka aka hana muminai fatan faruwar yaƙi, sai fa idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne ya ƙaddara faruwarsa, to sai su yi haƙuri su jajirce.

4. Babban abin da yake yin tasiri wajen samun kyakkyawa ko mummunan sakamako daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne niyyar bawa, ba kawai abin da yake na zahirin aikinsa ba.

5. Tabbatar da cewa, Annabi (ﷺ) mutum ne kamar sauran annabawa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko. Ya rayu har ya isar da saƙon da aka aiko shi da shi, kuma ya rasu ya koma ga Ubangijinsa; don haka ba ya nan a duniya kamar yadda wasu suke riyawa.

Suratu Ali-Imran (142-145)

أَمْ حَسِبْتُمْ أَن تَدْخُلُواْ ٱلْجَنَّةَ وَلَمَّا يَعْلَمِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ جَٰهَدُواْ مِنكُمْ وَيَعْلَمَ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿١٤٢﴾ وَلَقَدْ كُنتُمْ تَمَنَّوْنَ ٱلْمَوْتَ مِن قَبْلِ أَن تَلْقَوْهُ فَقَدْ رَأَيْتُمُوهُ وَأَنتُمْ تَنظُرُونَ ﴿١٤٣﴾ وَمَا مُحَمَّدٌ إِلَّا رَسُولٌ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهِ ٱلرُّسُلُ ۚ أَفَإِيْن مَّاتَ أَوْ قُتِلَ ٱنقَلَبْتُمْ عَلَىٰٓ أَعْقَٰبِكُمْ ۚ وَمَن يَنقَلِبْ عَلَىٰ عَقِبَيْهِ فَلَن يَضُرَّ ٱللَّهَ شَيْـًٔا ۗ وَسَيَجْزِى ٱللَّهُ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿١٤٤﴾ وَمَا كَانَ لِنَفْسٍ أَن تَمُوتَ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ كِتَٰبًا مُّؤَجَّلًا ۗ وَمَن يُرِدْ ثَوَابَ ٱلدُّنْيَا نُؤْتِهِۦ مِنْهَا وَمَن يُرِدْ ثَوَابَ ٱلْءَاخِرَةِ نُؤْتِهِۦ مِنْهَا ۚ وَسَنَجْزِى ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿١٤٥﴾

142. Yanzu kuna tsammanin za ku shiga Aljanna ne alhalin Allah bai bayyanar da masu yin jihadi daga cikinku ba, kuma bai bayyanar da masu haƙuri ba.

143. Kuma haƙiƙa kun kasance a da can kuna ta burin mutuwa tun kafin ku gamu da ita, to haƙiƙa (a yau) ga ta kun gan ta alhali kuna kallo da ido.

144. Kuma Muhammadu ba wani ne ba face Manzo kawai wanda manzanni haƙiƙa sun shuɗe gabaninsa. Shin yanzu idan ya mutu ko aka kashe shi, sai ku juya baya a kan dugaduganku? Duk kuwa wanda ya juya baya a kan dugadugansa to ba zai cuci Allah da komai ba. Kuma da sannu Allah zai saka wa masu godiya.

145. Kuma babu wani rai da zai mutu sai da izinin Allah, rubutaccen abu ne ƙayyadajje. Kuma duk wanda yake nufin sakamakon duniya, za Mu ba shi ita, wanda kuma yake nufin sakamakon lahira, to za Mu ba shi ita. Kuma da sannu za Mu saka ma masu godiya.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana nuna kuskuren muminai masu zaton cewa za su shiga Aljanna don kawai sun yi imani, ba tare da Allah ya jarrabe su ya tantance masu jihadi dominsa da kuma masu haƙuri.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tuna musu cewa, sun kasance a baya suna fatan haɗuwarsu da abokan gabarsu, suna mararin su yi mutuwar shahada; to ga shi a ranar Uhudu sun ga mutuwar da idanunsu, kuma sun kasa jurewa su yi haƙuri, har su kai ga samun abin da suke fatan su samu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cewa, Annabi (ﷺ) ba mai dawwama ne a duniya ba; shi ma kamar sauran annabawa yake; wasu daga cikinsu mutuwa suka yi, wasu kuma kashe su aka yi. To yanzu idan shi ma ajalinsa ya ƙare ta hanayar mutuwa ko kisa, shi ke nan sai su yi ridda su bar addininsu? To wanda duk ya yi ridda ya bar addinin Allah, to ba zai cutar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da komai ba, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai saka wa masu godiya daga cikin bayinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, babu wani rai a duniya da zai mutu sai da izinin Allah, wato idan ajalinsa ya yi. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yana ba wa kowa sakamakon aikinsa daidai da niyyarsa; wanda ya yi aikinsa don neman duniya, to sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi wani abu daga cikinta; wanda kuma ya yi aikinsa don neman ladan lahira, shi ma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi wani abu daga cikinta, kuma zai saka wa masu godiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yin koyi da magabata nagari daga cikin al'ummomin da suka gabace mu.

2. Wanda duk ya yi haƙuri a wajen biyayya ga Allah Ta'ala, bai nuna gazawa ba ko raki, to wannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai so shi.

3. Wanda duk zai dogara da dabararsa da ƙarfinsa wajen neman biyan buƙatarsa, to zai gamu da cikas da ƙaskanci, amma wanda zai riƙa addu'a da komawa ga Allah, yana neman taimakonsa, to wannan shi ne mai samun biyan buƙatarsa.

4. Gabatar da tuba da neman gafara a lokacin addu'a yayin da wani bala'i ya sauka. Domin duk wani bala'i da zai auku a duniya, to yana aukuwa ne saboda zunubban ɗan'adam, don haka ba abin da zai yaye shi, sai tuba da neman gafara.

Suratu Ali-Imran (146-148)

وَكَأَيِّن مِّن نَّبِيٍّ قَٰتَلَ مَعَهُۥ رِبِّيُّونَ كَثِيرٌ فَمَا وَهَنُواْ لِمَآ أَصَابَهُمْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَمَا ضَعُفُواْ وَمَا ٱسْتَكَانُواْ ۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلصَّٰبِرِينَ ﴿١٤٦﴾ وَمَا كَانَ قَوْلَهُمْ إِلَّآ أَن قَالُواْ رَبَّنَا ٱغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَا وَإِسْرَافَنَا فِىٓ أَمْرِنَا وَثَبِّتْ أَقْدَامَنَا وَٱنصُرْنَا عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿١٤٧﴾ فَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ ثَوَابَ ٱلدُّنْيَا وَحُسْنَ ثَوَابِ ٱلْءَاخِرَةِ ۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿١٤٨﴾

146. Kuma sau da yawa an sami wani annabi (daga cikin annabawa), mabiya masu yawa sun yi yaƙi tare da shi, amma ba su taɓa yin rauni ba saboda abin da ya same su a tafarkin Allah, kuma ba su taɓa yin ragwanci ba, kuma ba su taɓa miƙa wuya ba. Kuma Allah Yana son masu haƙuri.
147. Kuma ba su da wata magana sai faɗar: "Ya Ubangijinmu, Ka gafarta mana zunubanmu da ƙetare iyakar da muka yi cikin lamurranmu, kuma Ka tabbatar da dugaduganmu, kuma Ka taimake mu a kan mutunen da suke kafirai.

148. Sai Allah Ya ba su ladan duniya da kyakkyawan lada na lahira. Kuma Allah Yana son masu kyautatawa.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin abin da ya faru ga muminai a ranar yaƙin Uhudu, sanda aka samu cikas a yaƙin, har wasu daga cikinsu suka gudu daga fagen daga, sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, hanyar mabiya annabawa iri ɗaya ce, watau haƙuri da juriya a wurin jihadi, saboda haka su ma bai dace da su gudu ba.
A kan wannan ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ba da labarin cewa, sau da yawa wani annabi daga cikin annabawa yakan yi yaƙi tare da mabiyansa masu yawa, kuma wani rauni ya same su a yaƙin, amma hakan bai sa sun karaya sun rabu da addininsu ko sun watsar da jihadin ɗaukaka kalmar Allah ba; jikinsu bai yi sanyi ba, zukatansu ba su yi rauni ba, himmarsu ba ta dakushe ba, ba su ba maƙiyansu kai bori ya hau ba. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake son masu haƙuri irin waɗannan.Bugu da ƙari, duk irin abin da ya sami waɗannan jarumai a yaƙe-yaƙensu, ba abin da suke furtawa da bakunansu sai kawai neman gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a kan zunubbansu ko abin da suka ƙetare iyakar Ubangijinsu a cikin lamuransu. Suna kuma roƙon sa ya ba su ikon jajircewa, ya kuma ba su nasara a kan maƙiyansu kafirai. A sakamakon haka, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu kyakkyawar sakayya ta duniya, ya ba su nasara da ganima da ɗaukaka, kuma ga kyakkyawan sakamako na lahira, suka cim ma yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da dawwama a gidan Aljanna. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa yana son masu kyautatawa, don haka ne ya yi musu kyautayinsa a duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi ga muminai da kada su sake su biye ma ta maƙiyansu kafirai; wannan zai sa su yi ta jan su a hankali har su kai su ga yin ridda su bar Musulunci.

2. Gargaɗi game da yin shirka, wadda ita ce ke janyo bala’i a duniya da lahira. Kuma masu yin shirka koyaushe a tsorace suke, kuma za su gamu da azabar lahira ne.

3. Jayayya da saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) suna daga cikin abubuwan da ke jawo rashin cin nasara.

4. Kwaɗaitarwa a kan haɗin kai tsakanin Musulmi.

5. Wajibi jagoran mayaƙa ya zama jarumi, maras tsoro, wanda zai yi ƙoƙarin tattaro mayaƙansa idan an sami matsalar da ta sa wasu daga cikinsu suka gudu daga fagen yaƙi.

6. Bayyana jarumtar Annabi (ﷺ) a fagen yaƙi da rashin tsoronsa ga abokan gaba.

7. Mutum ya saɓa wa Allah bayan wata ni’ima da ya yi masa, ya fi girma da tsanani fiye da wanda ya yi saɓo ba cikin ni’ima ba, shi ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: “Kuma daga ƙarshe kuka saba bayan ya nuna muku abin da kuke so.”

8. Sahabbbai ba ma’asumai ne ba; sukan yi laifi, sai dai sukan gaggauta tuba, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma yana yafe musu.
9. Tarbiyantar da muminai a kan cewa, kada su riƙa nuna damuwa a kan wata jarrabawa da ta same su. Domin abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara faruwarsa shi ne yake faruwa, kuma baƙin ciki ba ya dawo da abin da aka rasa, sai dai ya ƙara wa bawa wani sabon bala’in, domin zai hana shi aikata komai na maslahar rayuwarsa.

10. Allah yana duba zukatan bayinsa ne. Duk sa’adda zuciya ta gyaru; to aiki ma zai gyaru, amma idan ta ɓace, to aikin ma sai ya ɓace.

11. Babu wanda zai iya kauce wa ƙaddara, ƙowane irin mataki kuwa zai ɗauka.

12. Aikata zunubi yakan jawo wani zunubin, kamar yadda aikata alheri yakan haifar da wani alheri a bayansa.

Suratu Ali-Imran (149-155)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تُطِيعُواْ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يَرُدُّوكُمْ عَلَىٰٓ أَعْقَـٰبِكُمْ فَتَنقَلِبُواْ خَـٰسِرِينَ ﴿١٤٩﴾ بَلِ ٱللَّهُ مَوْلَىٰكُمْ ۖ وَهُوَ خَيْرُ ٱلنَّـٰصِرِينَ ﴿١٥٠﴾
سَنُلْقِى فِى قُلُوبِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلرُّعْبَ بِمَآ أَشْرَكُواْ بِٱللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ سُلْطَـٰنًا ۖ وَمَأْوَىٰهُمُ ٱلنَّارُ ۖ وَبِئْسَ مَثْوَى ٱلظَّـٰلِمِينَ ﴿١٥١﴾ وَلَقَدْ
صَدَقَكُمُ ٱللَّهُ وَعْدَهُۥٓ إِذْ تَحُسُّونَهُم بِإِذْنِهِۦ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا فَشِلْتُمْ وَتَنَـٰزَعْتُمْ فِى ٱلْأَمْرِ وَعَصَيْتُم مِّنۢ بَعْدِ مَآ أَرَىٰكُم مَّا تُحِبُّونَ ۚ مِنكُم مَّن يُرِيدُ
ٱلدُّنْيَا وَمِنكُم مَّن يُرِيدُ ٱلْـَٔاخِرَةَ ۚ ثُمَّ صَرَفَكُمْ عَنْهُمْ لِيَبْتَلِيَكُمْ ۖ وَلَقَدْ عَفَا عَنكُمْ ۗ وَٱللَّهُ ذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٥٢﴾ ۞ إِذْ تُصْعِدُونَ وَلَا
تَلْوُۥنَ عَلَىٰٓ أَحَدٍ وَٱلرَّسُولُ يَدْعُوكُمْ فِىٓ أُخْرَىٰكُمْ فَأَثَـٰبَكُمْ غَمًّۢا بِغَمٍّ لِّكَيْلَا تَحْزَنُواْ عَلَىٰ مَا فَاتَكُمْ وَلَا مَآ أَصَابَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ خَبِيرٌۢ بِمَا
تَعْمَلُونَ ﴿١٥٣﴾ ثُمَّ أَنزَلَ عَلَيْكُم مِّنۢ بَعْدِ ٱلْغَمِّ أَمَنَةً نُّعَاسًا يَغْشَىٰ طَآئِفَةً مِّنكُمْ ۖ وَطَآئِفَةٌ قَدْ أَهَمَّتْهُمْ أَنفُسُهُمْ يَظُنُّونَ بِٱللَّهِ غَيْرَ ٱلْحَقِّ ظَنَّ
ٱلْجَـٰهِلِيَّةِ ۖ يَقُولُونَ هَل لَّنَا مِنَ ٱلْأَمْرِ مِن شَىْءٍ ۗ قُلْ إِنَّ ٱلْأَمْرَ كُلَّهُۥ لِلَّهِ ۗ يُخْفُونَ فِىٓ أَنفُسِهِم مَّا لَا يُبْدُونَ لَكَ ۖ يَقُولُونَ لَوْ كَانَ لَنَا مِنَ ٱلْأَمْرِ
شَىْءٌ مَّا قُتِلْنَا هَـٰهُنَا ۗ قُل لَّوْ كُنتُمْ فِى بُيُوتِكُمْ لَبَرَزَ ٱلَّذِينَ كُتِبَ عَلَيْهِمُ ٱلْقَتْلُ إِلَىٰ مَضَاجِعِهِمْ ۖ وَلِيَبْتَلِىَ ٱللَّهُ مَا فِى صُدُورِكُمْ وَلِيُمَحِّصَ مَا

فِي قُلُوبِكُمۡۚ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ١٥٤ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَوَلَّوۡاْ مِنكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡتَقَى ٱلۡجَمۡعَانِ إِنَّمَا ٱسۡتَزَلَّهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ بِبَعۡضِ مَا كَسَبُواْۖ وَلَقَدۡ عَفَا ٱللَّهُ عَنۡهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ حَلِيمٞ ١٥٥

149. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan har kuka yi biyayya ga waɗanda suka kafirta, to za su mayar da ku baya a kan dugaduganku, sai ku juya kuna hasararru.

150. A'a, Allah Shi ne Majiɓincin lamarinku; kuma Shi ne Fiyayyen masu taimako.

151. Da sannu za Mu jefa tsoro a cikin zukatan waɗanda suka kafirta saboda abin da suka yi na sanya wa Allah kishiya, abin da bai saukar da hujja a kai ba; kuma makomarsu ita ce wuta. Kuma tir da makomar azzalumai (idan ta zama wuta).

152. Kuma tabbas haƙiƙa Allah Ya cika muku alƙawarinsa yayin da kuka dinga kisan su da yawa da izininsa; har zuwa lokacin da kuka yi rauni, kuma kuka yi jayayya a cikin umarnin (Manzo), kuma daga ƙarshe kuka saɓa bayan (Allah) Ya nuna muku irin abin da kuke so. Cikinku akwai waɗanda suke nufin duniya, kuma cikinku akwai waɗanda suke nufin lahira. Sannan sai Ya kautar da ku kuka bar su don ya jarrabe ku; kuma tabbas haƙiƙa Allah Ya yi muku afuwa. Kuma Allah Ma'abocin falala ne ga muminai.

153. Ka tuna lokacin da kuke gudowa ba kwa waiwaye ma ku ga wanda yake baya da ku, kuma Manzo yana can bayanku yana ta kiran ku, sai (Allah) Ya saka muku da damuwa bisa damuwa domin kar ku yi baƙin ciki a kan abin da ya kuɓuce muku, da abin da ya same ku. Allah kuma Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne.

154. Sannan bayan damuwa sai (Allah) Ya saukar muku da kwanciyar hankali har gyangyaɗi yana ɗaukar wasu daga cikinku; amma wani sashin kuma tasu ta ishe su, suna yi wa Allah zato wanda ba na gaskiya ba, zato irin na jahiliyya; suna cewa: "Anya kuwa muna da ta cewa cikin wannan lamari?" Ka ce: "Lalle al'amari gaba ɗaya na Allah ne." Suna ɓoyewa a cikin rayukansu abin da ba sa bayyana maka shi; suna cewa: "In da al'amarin a hannunmu yake ai da ba a kashe mu a nan ba." Ka ce: "Ko da kun kasance kuna cikin gidajenku, tabbas da waɗanda aka rubuta za su mutu sun fito da kansu, sun zo inda nan ne za su kwanta (dama)." Kuma Allah (Ya ƙaddara haka) don Ya jarraba abin da yake cikin ƙirazanku, kuma don Ya tace abin da yake cikin zukatanku. Kuma Allah Masanin abin da yake cikin zukata ne.

155. Lalle waɗanda suka gudu daga cikinku yayin da runduna biyu suka haɗu, Shaiɗan ne ya so ya zamar da su saboda wani laifi da suka yi; kuma tabbas haƙiƙa Allah Ya yi musu afuwa. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai haƙuri.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gargaɗin muminai ne da kada su boye wa ta kafirai, domin yi musu biyayya zai iya jefa su cikin kafirci, su halaka duniya da lahira. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai jiɓintar lamarin bayinsa, kuma shi ne mai ba da nasara; su kuma kafirai ba wata nasara ko taimako da za su iya ba muminai.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa muminai albishir cewa, zai jefa tsoro a cikin zukatan kafirai, saboda shirkar da suke yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba tare da wata hujja ko wani dalili ba, a lahira kuma wutar Jahannama ce makomarsu, tir kuwa da wannan irin makoma ta azzalumai.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da tunatar da sahabban Annabi (ﷺ) matsalar da aka samu a yaƙin Uhudu ta ɓangaren wasu daga cikinsu saboda saɓa wa umarnin Annabi (ﷺ) da suka yi, bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya cika musu alƙawarin da ya yi musu na ba su nasara a kan abokan

gabarsu. Da farko Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗora muminai a kan kafirai, har sun fara kashe su, sai kuma Musulmi suka fara ja da baya a sakamakon saɓanin da ya ɓarke tsakanin maharba hamsin da Annabi (ﷺ) ya ajiye su a kan wani ɓangare na dutsen Uhudu, ya umarce su da kada su bar wannan wurin ko da kuwa sun ga alamun cin nasara tare da Musulmi. To amma sai suka saɓa wannan umarni yayin da suka ga Musulmi sun fara cin nasara a kan kafirai, suna bin su da sara da suka, sai kuma wasu suka tafi suna kwasar ganima, suka bar wurin tsayuwarsu, amma wasu sun ci gaba da tsayuwa inda aka tsayar da su. Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya juyar da lamarin muminai, galaba ta tabbata ga kafirai, suka juyo kan Musulmi da sara da suka ta gaba ta baya.

Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya kara masa yarda) ya ba mu labarin abin da ya faru a ranar Uhudu ya ce: “Mun haɗu a filin yaƙi tare da mushrikai, Annabi (ﷺ) ya ajiye wasu maharba a kan wani dutse, ya shugabantar musu da wani sahabi ana kiran sa Abdullahi ɗan Jubair (Allah ya kara masa yarda), ya kuma faɗa musu cewa: “Kada ku bar wurarenku ko da kuwa kun ga mu ne muka yi galaba a kansu ko kuma kun ga sun yi galaba a kanmu, to kada ku taho taimaka mana.” Jabir ya ce: “Yayin da muka fara fafatawa da su, sai suka ranta a na kare, muka ga mata suna ta gudu suna hawan duwatsu, sun buɗe ƙwaurinsu ana ganin mundayensu. Da maharban nan na kan dutse suka ga haka, sai suka riƙa cewa: “Ganima! Ganima!!” Sai Shugabansu Abdullahi ya ce musu: “Annabi (ﷺ) fa ya umarce mu da kada mu bar wurarenmu.” Sai suka ƙi jin maganarsa, suka shiga kwasar ganima. Haka na faruwa, sai reshe ya juye da mujiya, mushirikai suka yiwo kansu, har suka kashe sahabbai saba’in. Daga nan Abu Sufyan ya leƙo yana cewa: “Muhammadu na cikinku? Ɗan Abu Kuhafata yana cikinku? Ɗan Khaɗɗab yana cikinku?” Duk Annabi (ﷺ) yana ce wa sahabbai: “Kada ku amsa masa.” Sai Abu Sufyan ya ce: “Duk an kashe waɗannan. Da a ce suna da rai, da sun amsa.” Sai Umar ya kasa haƙuri, ya ce: “Karya kake maƙiyin Allah! Allah ya bar maka abin da zai ci gaba da tozarta ka.” Sai Abu Sufyan ya ce: “Sama dai, sama dai gunkin Hubal.” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Ku ba shi amsa.” Sai suka ce: “Me za mu ce masa?” Sai ya ce: “Ku ce: “Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne mafi ɗaukaka, kuma mafi girma.” Sai Abu Sufyan ya ce: “Muna da Uzza, amma ku ba ku da Uzza.” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Ku ba shi amsa.” Sai suka ce: “Me za mu ce?” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Ku ce Allah ne mai jiɓintar mu, ku ba ku da mai jiɓintar ku.” Sai Abu Sufyan ya ce: “Wannan rana ta zama a madadin ranar Badar. Yaƙi yau nasara gare ka ne, gobe ga maƙiyanka. Za ku ga wanda aka daddatsa shi bayan an kashe shi cikin mutanenku, ba ni ne na yi umarni da hakan ba, amma kuma bai baƙanta mini rai ba.” [Bukhari #4043]. Yana nufin abin da aka yi wa Sayyidina Hamza na fasa cikinsa da ciro kayan cikinsa.

Wannan jarraba ce da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa muminai don ya bambance mai biyayya daga cikinsu da wanda ya fanɗare. To amma kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce ya yafe musu, domin haka yake yin falalarsa ga muminai.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da tunatar da su lokacin da suka fita a guje ba mai waiwayen wani, a lokacin kuma Annabi (ﷺ) yana ta kiran su, yana neman su da su tsaya su daina gudu; to amma ina, sun bar shi a bayansu, ba sa amsa kiransa, sai a sakamakon haka Allah ya jefa musu wani baƙin ciki a zukatansu, inda aka baza jita-jitar cewa an kashe Annabi (ﷺ), Wannan ya zarce sauran ababen baƙin cikin da ya same su a wannan ranar, na rashin samun nasara ko ganima, da kashe wasu daga cikinsu, da yi wa wasu rauni.

Bayan wannan baƙin ciki ne sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa muminai nutsuwa, har wasu daga cikinsu suka riƙa gyangyaɗi. An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Abu Ɗalhata (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Na ɗaga kaina ranar yaƙin Uhudu na duba, kowa na gani a ranar gyangyaɗi yake ta bayan garkuwarsa, shi ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: “Sannan ya saukar muku da aminci bayan damuwar da kuka sami kanku a ciki, har gyangyaɗi ya riƙa lulluɓe wasu daga cikinku.” [Tirmizi #3007]. Wasu kuwa suka kasa samun nutsuwa suna tunanin kada a kashe su, waɗannan su ne munafuƙai, waɗanda suka riƙa yi wa Allah mummunan zato suna cewa, ba zai taimaka wa muminai da nasara ba. Wannan kuwa zato ne irin na jahilai waɗanda ba su san Allah ba. Har ma ta kai suna cewa, su tilas ce ta sa suka fito wannan yaƙin, don maganar ba a hannunsu take

ba, da a hannunsu take da ba a fito ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa ya mayar musu da martini da cewa, ai duk al'amura suna hannun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne shi kaɗai. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana siffofin munafukai da cewa, suna ɓoye wani abu a ransu wanda ba sa bayyana shi ga Annabi (ﷺ), watau maganar da suke yi a tsakaninsu cewa, da a ce suna da zaɓi a kan fitowa wannan yaƙi, da ba su zaɓi fitowa daga Madina ba, kuma da yanzu ba a kashe kowa ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa ya faɗa musu cewa, ai ko da suna gidajensu ba su fito wurin yaƙi ba, da sai waɗanda Allah ya rubuta mutuwarsu sun fito zuwa inda za su mutu, don haka ya kamata su san da cewa, daga Allah ne ƙaddara fitowarsu take, ba daga gare su ba, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi haka ne don ya jarraba abin da yake cikin zukatansu, ya fito da mai kyau da maras kyau. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san abin da bayinsa suke ɓoyewa a zukatansu, zai yi wa kowa hisabi gwargwadon aikinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, gudun da wasu sahabbai suka yi daga fagen yaƙi a wannan rana, ai Shaiɗan ne ya ingiza su ciki, kuma ya sami wannan damar ne a kansu saboda wasu laifuffukansu, amma duk da haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce ya yafe musu. Allah kuma mai yawan gafara ne, mai yawan haƙuri.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ilimin Allah da Ƙaddararsa babu wanda ya isa ya canza su. Wanda Allah ya ƙaddara wa rayuwa, don ya fita jihadi wannan ba zai sa shi ya mutu ba, hakanan wanda ya ƙaddara mutuwarsa, rashin fitarsa jihadi ba zai hana masa mutuwa ba. To gara ma ya yi mutuwar da take mafificiya a wurin Allah Ta'ala, ita ce mutuwar shahada, domin duka dai ƙarshe makomar ɗaya ce, to amma sakamakon ya sha bamban.
2. Allah ya haɗa tsakanin gafara da rahama, domin farin cikin ɗan'adam ya cika. Gafara tana nufin kawar masa da abin ƙi, rahama kuma tana nufin samun abin da yake ƙauna.

Suratu Ali-Imran (156-158)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَقَالُواْ لِإِخۡوَٰنِهِمۡ إِذَا ضَرَبُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَوۡ كَانُواْ غُزًّى لَّوۡ كَانُواْ عِندَنَا مَا مَاتُواْ وَمَا قُتِلُواْ لِيَجۡعَلَ ٱللَّهُ ذَٰلِكَ حَسۡرَةٗ فِي قُلُوبِهِمۡۗ وَٱللَّهُ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ١٥٦ وَلَئِن قُتِلۡتُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ أَوۡ مُتُّمۡ لَمَغۡفِرَةٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَحۡمَةٌ خَيۡرٞ مِّمَّا يَجۡمَعُونَ ١٥٧ وَلَئِن مُّتُّمۡ أَوۡ قُتِلۡتُمۡ لَإِلَى ٱللَّهِ تُحۡشَرُونَ ١٥٨

156. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kasance kamar waɗanda suka kafirta, kuma suka riƙa faɗa wa 'yan'uwansu yayin da suka yi tafiya a bayan ƙasa, ko kuma suka kasance mayaƙa: "In da sun kasance tare da mu, ai da ba su mutu ba, kuma da ba a kashe su ba," don Allah Ya sanya waccan (maganar) ta zamo nadama a cikin zukatansu. Kuma Allah Shi ne Mai rayawa, kuma Shi ne Mai kashewa. Kuma Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

157. Kuma lalle idan ma har an kashe ku a hanyar Allah ko kuma kuka mutu, to kuna da gafara ta musamman a wajen Allah da kuma rahama, wanda shi ne mafi alheri fiye da abin da suke tarawa.

158. Kuma lalle in kuka mutu ko aka kashe ku, lalle zuwa ga Allah dai za a mayar da ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa muminai kashedi daga yin munanan maganganu irin na kafirai masu nuna rashin imani da Kaddarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Watau sun saba duk lokacin da 'yan'uwansu kafirai suka yi tafiya ta kasuwanci ko yaƙi, sai Allah ya ƙaddari mutuwarsu a can, sai 'yan'uwan nasu kafirai su riƙa cewa, da ba su fita ko'ina ba sun yi zamansu a garuruwansu da hakan bai faru gare su ba. Wannan irin muguwar aƙida ita ta sa Allah ya sanya musu

nadama a zukatansu, masifarsu kuma ta yi ta ƙaruwa. Sun manta da cewa Allah shi kaɗai yake da ikon rayawa da kashewa; babu wani rai da zai mutu har sai ajalinsa ya cika, Allah kuma yana ganin duk abin da bayinsa suke aikatawa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa muminai cewa, duk wanda aka kashe shi ko ya mutu wajen ɗaukaka Kalmar Allah, to abin da zai samu na gafarar Allah da rahamarsa, ya fi masa alheri fiye da zamansa a duniya da abin da masu tara dukiya a duniya suke tarawa. Allah kuma ya sake tuna musa cewa, ko mutuwa suka yi ko kuma kashe su aka yi, to makoma dai zuwa ga Allah take.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a kan kyawawan halaye da tausasawa wajen mu'amala, domin yin haka ne yake kawo haɗin kai na al'umma, ya haifar da soyayyar juna; rashinsa kuma shi ne yake haifar da rarrabuwar kai da ƙiyayyar juna.

2. Kyawawan halayen shugaba na addini sukan sa mutane su gane addinin, su karɓe shi, yayin da miyagun halayensa kan iya sa mutane su nisanci addinin, su tsane shi.

3. Neman shawara ibada ce da mai yin ta zai sami kusanci ga Allah.

4. A cikin neman shawara akwai hikimomi da yawa, daga cikinsu akwai:
• Hana shugaba yin mulkin kama-karya.
• Koya wa mutane yaddda za su gudanar da al'amuransu, su sami gogewa a kai.
• Koyar da tawali'u wajen neman shawara. Domin duk shugaban da yake neman shawara a kan lamuransa, wannan yana nuna shi mai tawali'u ne.
• Motsa kuzarin al'umma. Yayin da za su ga ana neman shawararsu wannan zai ƙara musu kuzari a kan ayyukan alheri.
• Idan ra'ayoyi daban-daban suka haɗu tare da kyakkyawar niyya, sau tari akan dace da daidai. Domin mutum shi kaɗai zai iya hango maslahar wani al'amari, amma ya kasa gano ɓarnar da ke cikinsa, musamman ma idan idonsa ya rufe wajen son wannan abu; to amma bayan an yi shawara sai a gane duk abin da ke ciki na maslaha da na ɓarna.
• Idan an gudanar da kowane abu ta hanyar shawara, to ba za a sami rarrabuwar jama'a ba, domin karɓaɓɓun mutane masu gaskiya da gogewa a cikin al'amura, su ne ake neman shawararsu.

5. Haramun ne wani ya ci amanar wani, ko ya saci dukiyarsa. Kɛbance Annabi (ﷺ) da ambato a ƙira'ar da aka ce: "Bai kamata ba a ci amanar wani annabi…", yana nuna duk sanda wanda aka yi wa laifin ya zamanto babban mutum ne mai daraja, to laifin ya fi girma da tsanani. Manzon Allah (ﷺ) shi ne mafificin halitta, don haka yi masa laifi ya fi tsanani da muni. Sannan kuma shi Annabi (ﷺ) ana yi masa wahayi lokaci bayan lokaci, don haka duk wanda ya ha'ince shi, to wahayi na iya sauka nan take ya tona asirin mai ha'incin tun a duniya, baya ga azabar lahira idan ya mutu bai tuba ba. Sannan kuma Musulmi a lokacin suna cikin matsanancin talauci, don haka ha'inci a sannan yake da matuƙar muni.

6. Dogaro ga Allah yana nufin mutum ya riƙe sabubba tare da mayar da al'amarinsa ga Allah.

7. Idan mutum ya bi dukkan hanyoyi da suka cancanta wajen neman wani abu ko aikata wani abu, sannan ya nemi taimakon Allah ta hanyar dogaro gare shi, to kada ya tsaya kai-komo wajen zartar da abin da ya yi ƙuduri, ta yadda al'amarinsa zai zamar masa damuwa da rashin kwanciyar hankali.

Suratu Ali-Imran (159-161)

فَبِمَا رَحۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ لِنتَ لَهُمۡۖ وَلَوۡ كُنتَ فَظًّا غَلِيظَ ٱلۡقَلۡبِ لَٱنفَضُّواْ مِنۡ حَوۡلِكَۖ فَٱعۡفُ عَنۡهُمۡ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لَهُمۡ وَشَاوِرۡهُمۡ فِي ٱلۡأَمۡرِۖ فَإِذَا عَزَمۡتَ فَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَوَكِّلِينَ ١٥٩ إِن يَنصُرۡكُمُ ٱللَّهُ فَلَا غَالِبَ لَكُمۡۖ وَإِن يَخۡذُلۡكُمۡ فَمَن ذَا ٱلَّذِي يَنصُرُكُم مِّنۢ بَعۡدِهِۦۗ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١٦٠ وَمَا كَانَ لِنَبِيٍّ أَن يَغُلَّۚ وَمَن يَغۡلُلۡ يَأۡتِ بِمَا غَلَّ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ ثُمَّ تُوَفَّىٰ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا كَسَبَتۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ١٦١

159. To saboda rahama ta musamman daga Allah, sai ka zamo mai tausasawa gare su; in da kuwa ka kasance mai kaushin mu'amala, mai ƙeƙasasshiyar zuciya ne, to da sun watse sun bar ka. To ka yi musu afuwa, kuma ka nema musu gafara, kuma ka nemi shawararsu cikin duk lamura; amma idan ka riga ka ƙulla niyya, to ka dogara ga Allah. Lalle Allah Yana son masu dogara a gare Shi.

160. Idan Allah Ya ba ku nasara, to ba wanda ya isa ya rinjaye ku, amma idan Ya taɓar da ku, to wane ne ya isa ya taimake ku in ba shi ba? Kuma muminai wajibi ne su dogara ga Allah Shi kaɗai.

161. Kuma bai dace ba ga wani annabi ya yi ha'inci. Duk wanda ya yi ha'inci kuwa zai zo da abin da ya ha'inta ranar tashin alƙiyama. Sannan kowane rai a cika masa (sakamakon) abin da ya aikata, kuma su (halitta) ba za a zalunce su ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabinsa cewa, saboda rahamar da Allah ya yi masa ne, ya sa ya zama mai sauƙin kai ga sahabbansa, mai tausasa musu mu'amala, don haka duk suka tattaru a wurinsa, suna bin umarninsa. Da abin a ce shi mai mummunan hali ne, mai kakkausar zuciya, to da duk sun watse sun bar shi.

An karɓo daga Aɗa'u ɗan Yasar ya ce: "Na gamu da Abdullahi da Amru ɗan Asi (Allah ya kara masa yarda), sai na ce masa: "Faɗa mini siffar Annabi (ﷺ) da take cikin littafin Attaura." Sai ya ce: "Kwarai an siffanta shi a Littafin Attaura da wasu siffofinsa da suke cikin Alƙur'ani, inda Allah yake cewa: "Ya kai wannan Annabi, lalle mun aiko ka a matsayin mai shaida, kuma mai albishir mai gargaɗi, kuma mai tsaron Ummiyyai, watau Larabawan da ba sa rubutu da karatu. Kai bawana ne, kuma Manzona, na sa maka suna 'Mai dogaro', ba mai mugun hali ba ko mai kaushin zuciya ko mai yawan hayaniya a kasuwanni ba, ba ya rama mummuna da mummuna, sai dai ya yi afuwa, ya yi gafara. Kuma Allah ba zai karɓi rayuwarsa ba, har sai bayan ya tsaida addini da shi, har mutane su furta Kalmar Shahada, wadda ita za ta buɗe idanun da suka makance da kunnuwan da suka kurumce da zukatan da suka toshe." [Bukhari #2124].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya yi afuwa a kan kurakuransu da gajiyawarsu, kuma ya nema musu gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya kuma nemi shawararsu cikin abubuwan da kan taso masu buƙatar sai an yi shawara. Bayan shawara kuma, duk abin da ya ga shi ne ya fi maslaha, to ya ci gaba da zartar da shi, ya dogara ga Allah, Allah yana son masu dogara da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa, idan har ya ƙaddara musu samun wata nasara, to babu wanda ya isa ya karya su ko ya ci galaba a kansu; idan kuwa ya yi watsi da su, ya ƙyale su, to har abada babu mai iya taimakon su, don haka lalle muminai su dogara da Allah shi kaɗai. Sannan Allah ya faɗakar da cewa, ba ya daga cikin halayen annabawa su saci dukiyar ganima, domin Allah ya tsare su daga cin amana ko wani mugun hali, don haka bai dace a tuhume su da wani abu irin wannan ba.

Yawancin makaranta sun karanta ayar kamar haka: (يُغَلّ أنْ) watau suka yi rufu'a a kan (يُ), suka kuma yi fataha a kan (غَ)). Ma'ana: "Bai kamata ba a ha'inci wani annabi...."
Sai kuma ya ambaci sakamakon wanda ya saci ɗukiyar ganima da cewa, zai zo ɗauke da kayanta a ranar gobe ƙiyama a gadon bayansa, sannan kowane rai za a yi masa sakayya a kan aikinsa, kuma babu wanda za a zalunta komai.

An karƀo daga Mu'azu ɗan Jabal (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya aike ni, bayan na kama hanya na tafi, sai kuma ya aika a kirawo ni. Da na dawo sai ya ce: "Ko ka san don me na aika a kirawo ka? Kada ka kuskura ka ɗauki wani abu na ganima ba tare da izinina ba, domin yin haka satar ɗukiyar ganima ce wanda duk ya saci ɗukiyar ganima, to zai zo da abin da ya sata ranar alƙiyama. Don haka ne na kirawo ka, sai ka tafi wurin aikinka." [Bukhari #200].

An karƀo daga Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Ranar yaƙin Khaibara, wasu sahabbai sun zo suna lissafa wa Manzon Allah (ﷺ) cewa, wane ya yi shahada, wane ma ya yi shahada, har suka zo kan wani mutum, sai suka ce, wane ma ya yi shahada." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "A'a, ba haka ba ne, ni na gan shi a wutar Jahannama saboda wani mayafi da ya sata daga ɗukiyar ganima." Sannan Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya kai ɗan Khaɗɗab, tafi ka yi shela a cikin mutane cewa, babu mai shiga Aljanna sai muminai kaɗai." Ya ce: "Sai na fita na shelanta wa mutane cewa, babu mai shiga Aljanna sai mumini kaɗai." [Muslim #114].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bawan da yake neman yardar Allah, yake aiki da umarninsa, ba zai taƀa zama ɗaya da wanda ya duƙufa a kan saƀon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba.
2. Musiba da taƀewa tana samun bawa ne a dalilin saƀon Allah da yake yi. Don haka tuba ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne maganin duk wata musifa, kamar yadda Allah ya bayyana a *Suratu Hud*, aya ta 3 da 52.

3. Halayyar mutum takan caccanza, wani lokaci ya zamanto ya fi kusa da kafirci, wani lokaci kuma ya dawo ya fi kusa da imani.

Suratu Ali-Imran (162-168)
أَفَمَنِ ٱتَّبَعَ رِضۡوَٰنَ ٱللَّهِ كَمَنۢ بَآءَ بِسَخَطٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَمَأۡوَىٰهُ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ١٦٢ هُمۡ دَرَجَٰتٌ عِندَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِمَا يَعۡمَلُونَ ١٦٣ لَقَدۡ مَنَّ ٱللَّهُ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ إِذۡ بَعَثَ فِيهِمۡ رَسُولٗا مِّنۡ أَنفُسِهِمۡ يَتۡلُواْ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمۡ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَإِن كَانُواْ مِن قَبۡلُ لَفِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ١٦٤ أَوَلَمَّآ أَصَٰبَتۡكُم مُّصِيبَةٞ قَدۡ أَصَبۡتُم مِّثۡلَيۡهَا قُلۡتُمۡ أَنَّىٰ هَٰذَاۖ قُلۡ هُوَ مِنۡ عِندِ أَنفُسِكُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١٦٥ وَمَآ أَصَٰبَكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡتَقَى ٱلۡجَمۡعَانِ فَبِإِذۡنِ ٱللَّهِ وَلِيَعۡلَمَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٦٦ وَلِيَعۡلَمَ ٱلَّذِينَ نَافَقُواْۚ وَقِيلَ لَهُمۡ تَعَالَوۡاْ قَٰتِلُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ أَوِ ٱدۡفَعُواْۖ قَالُواْ لَوۡ نَعۡلَمُ قِتَالٗا لَّٱتَّبَعۡنَٰكُمۡۗ هُمۡ لِلۡكُفۡرِ يَوۡمَئِذٍ أَقۡرَبُ مِنۡهُمۡ لِلۡإِيمَٰنِۚ يَقُولُونَ بِأَفۡوَٰهِهِم مَّا لَيۡسَ فِي قُلُوبِهِمۡۚ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا يَكۡتُمُونَ ١٦٧ ٱلَّذِينَ قَالُواْ لِإِخۡوَٰنِهِمۡ وَقَعَدُواْ لَوۡ أَطَاعُونَا مَا قُتِلُواْۗ قُلۡ فَٱدۡرَءُواْ عَنۡ أَنفُسِكُمُ ٱلۡمَوۡتَ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ١٦٨

162. Shin yanzu wanda ya bi yardar Allah, zai yi kamar wanda ya dawo da fushin Allah, kuma makomarsa ta zamo Jahannama? Kuma tir da wannan makoma.

163. Su darajoji ne a wajen Allah. Allah kuma Mai ganin abin da suke aikatawa ne.

164. Lalle haƙiƙa Allah Ya yi ni'ima ga muminai yayin da Ya aiko musu Manzo daga cikinsu, wanda yake karanta musu ayoyinsa, kuma yake tsarkake su, kuma yake koyar da su Littafi da Hikima, lalle kuma sun kasance kafin (zuwansa) tabbas suna cikin ɓata mabayyani.

165. Shin yayin da wata musifa ta same ku, wadda kuma haƙiƙa kun yi wa (kafirai) irinta ninki biyu, sai ku riƙa cewa: "Yaya haka ta faru?" Ka ce: "Ai wannan daga kanku ne." Lalle Allah Mai iko ne a kan komai.

166. Kuma abin da ya same ku ranar da ƙungiyoyin nan biyu suka haɗu, to da izinin Allah ne, kuma don Ya bayyana muminai.

167. Kuma don Ya bayyana waɗanda suka yi munafunci; kuma aka riƙa cewa da su: "Ku zo ku yi yaƙi don Allah ko don kariya." Sai suka ce: "Da mun san za a yi yaƙi ai da lalle mun biyo ku." Su a wannan lokacin sun fi kusanci ga kafirci fiye da imani, suna faɗi da bakunansu abin da ba ya cikin zukatansu. Kuma Allah Ya san abin da suke ɓoyewa.

168. Su ne waɗanda suka faɗa wa 'yan'uwansu, alhalin suna zaune a gida cewa: "In da sun bi (shawarar) mu da ba a kashe su ba." Ka ce: "To ku kare kanku daga mutuwa in har kun kasance masu gaskiya."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, wanda ya kasance yardar Allah ce abin nemansa da wanda ya riga ya dulmiya cikin saɓon Allah, ya dawo da fushinsa ba za su taɓa zama ɗaya ba, waɗannan kuma wutar Jahannama ita ce makomarsa. Tir kuma da wannan makoma. Allah kuma ya ƙara jaddada cewa, waɗanda suka nemi yardar Allah suna da matakai daban-daban na ɗaukaka; waɗanda kuma Allah ya yi fushi da su su ma suna da matakai daban-daban na ƙasƙanci. Kuma Allah yana ganin duk abin da bayinsa suke aikatawa, kuma zai yi musu sakayya a kansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin ni'imar da ya yi wa muminai, ta hanyar aiko musu da Manzo daga cikin jinsinsu na mutane, yana karanta musu Alƙur'ani, yana tsarkake su daga shirka da saɓon Allah da miyagun halayya, kuma yana koya musu ma'anonin Alƙur'ani da sunnarsa, duk da cewa kafin zuwan wannan Manzo, suna cikin ɓata mabayyani.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci muminai, lokacin da musiba ta same su a ranar yaƙin Uhudu, ta yi musabbabin kashe mutum saba'in, alhali su kuma sun yi sanadiyyar jawo musu musifa riɓi biyu, ta hanyar kashe musu mutum saba'in da kama mutum saba'in a yaƙin Badar, amma kuma sai suka riƙa tambayar yaya aka yi wannan musibar ta same su? Sai Allah ya umarci Annabinsa (ﷺ) ya faɗa musu cewa, abin da ya same su fa su ne suka jawo shi da kansu, lokacin da suka riƙa jayayya a kan umarnin Annabi (ﷺ), kuma suka saɓa wa umarninsa. Don haka Allah mai iko ne a kan yi musu uƙuba irin ta ranar yaƙin Uhudu, kuma yana da ikon ba su nasara, don haka kada su yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zaton da ba na gaskiya ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gaya wa muminai cewa, abin da ya same su a yaƙin Uhudu, lokacin haɗuwarsu da rundunar mushirikai, ya faru ne da nufin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da hukuncinsa, don ya tantance tsakanin muminai na gaskiya da munafuƙan da suke ɓoye cikin sahun Musulmi. Kuma ai asirinsu ya tonu lokacin da aka kirawo su su fito yaƙi na ɗaukaka addinin Allah, ko kuma don kare ƙasa da mutanen cikinta, sai kawai suka riƙa ba da wani hanzari na banza suna cewa, da sun san idan an fita za a fafata tsakanin musulmai da kafirai, da sai su fita, to amma suna ganin hakan ba zai faru ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, munafuƙai a wannan lokacin sun fi kusa da kafirci fiye da imani. Suna ɓoyewa a ransu, saɓanin abin da suke bayyanawa, kuma Allah yana ganin duk abin da suke ɓoyewa.
Munafuƙan da suka ƙi fita yaƙi dai sun riƙa ce wa danginsu da suka fita, aka kashe su, cewa: "Da sun karɓi shawararmu sun ƙi fita, ai da ba a kashe su ba." Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci

Annabinsa ya faɗa musu cewa, su masu ba da shawarar ai sai su kare kawunansu daga mutuwa, idan har su masu gaskiya ne, cewar da sun yi musu biyayya da ba a kashe su ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar waɗanda aka kashe su wajen yaɗa addinin Allah, kuma suna da wata rayuwa a ƙaburburansu wadda ta zarce rayuwarsu ta duniya a kamala da jin daɗi.

2. Tabbatar da samun ni'imar ƙabari ga bayin Allah na ƙwarai.

3. Muminai suna shiga Aljanna ne da falalar Ubangijinsu, ba don yawan aikinsu ba.

4. Abu ne mai kyau mumini ya taya ɗan'uwansa mumini farin ciki idan ya gan shi a cikin aikin biyayya ga Allah.

5. Tabbatar da adalcin Ubangiji da cewa ba ya tozarta ladan muminai.

Suratu Ali-Imran (169-171)

وَلَا تَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ قُتِلُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ أَمۡوَٰتَۢاۚ بَلۡ أَحۡيَآءٌ عِندَ رَبِّهِمۡ يُرۡزَقُونَ ١٦٩ فَرِحِينَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ وَيَسۡتَبۡشِرُونَ بِٱلَّذِينَ لَمۡ يَلۡحَقُواْ بِهِم مِّنۡ خَلۡفِهِمۡ أَلَّا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ١٧٠ يَسۡتَبۡشِرُونَ بِنِعۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَفَضۡلٖ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٧١

169. Kuma kada ka yi tsammanin waɗanda aka kashe su a wajen yaɗa kalmar Allah matattu ne. A'a, rayayyu ne a wajen Ubangijinsu, ana arzurta su.
170. Suna cike da farin cikin abin da Allah Ya ba su na falalarsa, kuma suna masu yin albishir ga waɗanda ba su riga sun riske su ba daga bayansu cewa, babu jin tsoro a gare su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

171. Suna ta farin ciki da ni'ima daga Allah da falala, kuma Allah ba Ya tozarta ladan masu imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabinsa da kada ya yi zaton cewa, sahabbansa da aka kashe a ranar Uhudu matattu ne; a'a su rayayyu ne wata rayuwa ta musamman a wurin Ubangijinsu, suna nan kusa da shi, suna jin daɗi da ni'imar da ya tanadar musu a gidan Aljanna, suna cike da farin ciki da irin manya-manyan ni'imomi da ya ba su. Hakanan suna yin albishir ga 'yan'uwansu waɗanda suka baro a duniya suna fafata yakin ɗaukaka kalmar Allah, suna cewa, su ma da zarar an kashe su a wannan yanayi, to za su sami saduwa da su, ba tare da sun ji tsoron abin da za su iske ba, ko baƙin cikin abin da suka bari a duniya. Za su yi farin ciki da albishir da karramawa da falalar da Allah ya yi musu. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya tozarta ladan muminai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lokacin da aka kashe 'yan'uwanku a yaƙin Uhudu, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya rayukansu a cikin cikkunan wasu korayen tsuntsaye, suna zuwa ƙoramun Aljanna suna sha, kuma suna cin kayan marmarinta, sannan su koma ga wasu fitilu na zinariya da ke rataye a inuwar Al-Arshi. Lokacin da suka sami abinci mai daɗi da abin sha mai daɗi da makwanci na alfarma, sai suka ce: 'Wane ne zai kai labarinmu ga 'yan'uwanmu cewa muna nan a Aljanna ana ciyar da mu, domin kada su guji jihadi su bar yaƙi?' Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: 'Ni ne zan kai musu labarinku.' Sai ya saukar da faɗarsa: 'Kuma kada ku yi tsammanin waɗanda aka kashe a wajen ɗaukaka kalmar Allah matattu ne, a'a, rayayyu ne a wajen Ubangijinsu ana arzuta su.' [Ahmad #2388, da Abu Dawud #2520].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan bawa bai amsa kiran Manzon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba, to bai amsa na Allah ba ke nan.

2. Falalar sahabban Annabi (ﷺ), yayin da raunin da ke jikinsu bai hana musu amsa kiran Allah da na Manzonsa ba.

3. Wajibi ne a kan muminai duk sa'adda suka samu kansu cikin wata matsala, to su nemi mafaka a wurin Allah da taimakonsa, babu mai kare muminai daga kowane sharri sai Allah shi kaɗai.

4. Imani yana ƙaruwa ta hanyar yi wa Allah biyayya, yana kuma raguwa ta hanyar saɓa masa.

5. Masu dogaro ga Allah su suke da kyakkyawan ƙarshe.

Suratu Ali-Imran (172-176)

ٱلَّذِينَ ٱسۡتَجَابُواْ لِلَّهِ وَٱلرَّسُولِ مِنۢ بَعۡدِ مَآ أَصَابَهُمُ ٱلۡقَرۡحُۚ لِلَّذِينَ أَحۡسَنُواْ مِنۡهُمۡ وَٱتَّقَوۡاْ أَجۡرٌ عَظِيمٌ ١٧٢ ٱلَّذِينَ قَالَ لَهُمُ ٱلنَّاسُ إِنَّ ٱلنَّاسَ قَدۡ جَمَعُواْ لَكُمۡ فَٱخۡشَوۡهُمۡ فَزَادَهُمۡ إِيمَٰنٗا وَقَالُواْ حَسۡبُنَا ٱللَّهُ وَنِعۡمَ ٱلۡوَكِيلُ ١٧٣ فَٱنقَلَبُواْ بِنِعۡمَةٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَفَضۡلٖ لَّمۡ يَمۡسَسۡهُمۡ سُوٓءٞ وَٱتَّبَعُواْ رِضۡوَٰنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ ذُو فَضۡلٍ عَظِيمٍ ١٧٤ إِنَّمَا ذَٰلِكُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ يُخَوِّفُ أَوۡلِيَآءَهُۥ فَلَا تَخَافُوهُمۡ وَخَافُونِ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١٧٥ وَلَا يَحۡزُنكَ ٱلَّذِينَ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡكُفۡرِۚ إِنَّهُمۡ لَن يَضُرُّواْ ٱللَّهَ شَيۡـٔٗاۗ يُرِيدُ ٱللَّهُ أَلَّا يَجۡعَلَ لَهُمۡ حَظّٗا فِي ٱلۡأٓخِرَةِۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٌ ١٧٦

172. Su ne waɗanda suka amsa kiran Allah da Manzo bayan miki ya same su a jikinsu. Lalle waɗanda suka kyautata a cikinsu, kuma suka yi taƙawa, suna da lada mai girma.

173. Su ne waɗanda mutane suka ce da su: "Lalle mutanen (Makka) fa sun tara muku runduna, to sai ku tsorace su." Amma sai hakan ya ƙara musu imani, sai suka riƙa cewa: "Allah Ya wadace mu, kuma madalla da abin dogara (idan har Shi ne Allah)."

174. (A sakamakon haka) sai suka dawo da ni'ima ta musamman daga Allah da falala, wani abin ƙi bai shafe su ba, kuma (suka dace da cewa) sun bi yardar Allah. Allah kuma Ma'abocin falala ne wadda take mai girma.

175. Wannan (labarin), Shaiɗan ne kawai yake tsoratar da ku masoyansa, don haka kar ku ji tsoron su, amma ku ji tsoro Na in dai har ku muminai ne.

176. Kuma kada waɗanda suke gaggawar shiga cikin (ayyukan) kafirci, su fusata ka. Haƙiƙa su ba za su cutar da Allah komai ba. Allah Ya yi nufin ba zai sanya musu wani rabo a lahira ba; kuma suna da azaba mai girma.

Yayin da Annabi (ﷺ) ya dawo Madina daga yaƙin Uhudu, sai ya sami labarin cewa, Abu Sufyana da mutanensa suna ƙoƙarin dawowa Madina, sai Annabi (ﷺ) ya nemi sahabbansa kowa ya fito har da masu raunuka, don su amsa kiran Allah da Manzonsa, suka nufi wani wuri da ake kira Hamra'ul Asad. Da suka isa wurin, sai wani ya zo yana ce musu: "Mutane fa sun yi muku taron dangi da nufin sai sun ga bayanku gaba ɗaya." Ya kuwa faɗa musu haka ne don ya tsorata su; to amma a maimakon su tsorata, sai wannan ya ƙara musu imani da dogaro ga Allah, suka ce: "Mu dai Allah ya ishe mu, kuma madalla da abin dogaro

Allah.” Sai ga shi sun dawo daga wannan wurin da wata ni’ima daga Allah da falala, ba abin da ya same su na cutarwa daga ɓangaren maƙiyansu, kuma sun bi yardar Allah lokacin da suka karɓa kiran Allah da Manzonsa, suka sake fitowa. Allah ma’abocin falala ne wadda take mai girma.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan da yake tsoratar da su ba wani ne ba Shaiɗan ne, kuma yana so ne ya shuka tsoron jama’arsa mushirikai a zukatan muminai. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce, kar wanda ya ji tsoron mushirikai; Allah kaɗai za su ji tsoro idan har su muminai ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samun ni’imar duniya ba dalili ne da yake nuna Allah ya yarda da wanda ya ba shi ni’imar ba, wannan ni’imar tana iya zama sanadiyyar azabtar da shi a lahira.

2. Ya wajaba mumini a kullum ya riƙa duba rayuwarsa a kan me yake tafiyar da ita, yana tafiyar da ita ne a kan ɗa’a ga Allah ko a kan saɓon Allah? Domin yawan rai yana amfanar mutum ne idan ya tafiyar da shi a cikin ɗa’ar Allah.

3. Ba a tantance mumini na gaskiya da munafuƙi a lokacin da ake cikin yalwa da ni’ima; ana tantancewa da su ne a lokacin da aka shiga wani tsanani ko bala’i.

4. Rowa tana daga cikin manyan laifukan da Allah zai yi wa bawa uƙuba a kansu.

Suratu Ali-Imran (177-180)
إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱشۡتَرَوُاْ ٱلۡكُفۡرَ بِٱلۡإِيمَٰنِ لَن يَضُرُّواْ ٱللَّهَ شَيۡـٔٗاۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١٧٧ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَنَّمَا نُمۡلِي لَهُمۡ خَيۡرٞ لِّأَنفُسِهِمۡۚ إِنَّمَا نُمۡلِي لَهُمۡ لِيَزۡدَادُوٓاْ إِثۡمٗاۚ وَلَهُمۡ عَذَابٞ مُّهِينٞ ١٧٨ مَّا كَانَ ٱللَّهُ لِيَذَرَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ عَلَىٰ مَآ أَنتُمۡ عَلَيۡهِ حَتَّىٰ يَمِيزَ ٱلۡخَبِيثَ مِنَ ٱلطَّيِّبِۗ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُطۡلِعَكُمۡ عَلَى ٱلۡغَيۡبِ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَجۡتَبِي مِن رُّسُلِهِۦ مَن يَشَآءُۖ فَـَٔامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦۚ وَإِن تُؤۡمِنُواْ وَتَتَّقُواْ فَلَكُمۡ أَجۡرٌ عَظِيمٞ ١٧٩ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ يَبۡخَلُونَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ هُوَ خَيۡرٗا لَّهُمۖ بَلۡ هُوَ شَرّٞ لَّهُمۡۖ سَيُطَوَّقُونَ مَا بَخِلُواْ بِهِۦ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ وَلِلَّهِ مِيرَٰثُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ١٨٠

177. Lalle waɗanda suka musanya imani da kafirci ba za su cutar da Allah da komai ba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi.

178. Kuma waɗanda suka kafirta kar su yi tsammanin cewa, jinkiri da Muke yi musu wani alheri ne ga kawunansu. Ai Muna saurara musu ne kawai don su ƙara laifi (a kan laifinsu). Kuma suna da azaba mai wulaƙantarwa.

179. Da ɗai Allah ba zai ƙyale muminai a yadda kuke ɗin nan ba har sai Ya rarrabe tsakanin lalatacce da kyakkyawa. Kuma Allah ba zai sanar da ku gaibu ba, sai dai Allah Yana zaɓar wanda Ya so cikin manzanninsa ne; don haka ku ƙara yin imani da Allah da manzanninsa. Idan kun yi imani, kun yi taƙawa kuwa, to kuna da lada mai girma.

180. Kuma waɗanda suke yin rowar abin da Allah Ya ba su na falalarsa kar su yi tsammanin hakan alheri ne a gare su; a’a, hakan sharri ne a gare su; da sannu za a yi musu saƙandami da abin da suka yi rowa da shi a ranar alƙiyama. Kuma Allah Shi ne Mai gadon sammai da ƙasa. Kuma Allah Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin waɗanda suka musanya imani da kafirci cewa, ba za su cuci Allah da komai ba; kawunansu kaɗai za su cuta, domin za su cancanci uƙubar Allah ne mai tsanani.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabinsa (ﷺ) cewa, kada ya yi zato, su ma kafirai kar su yi zaton rashin gaggauto musu da azabar Allah da ƙyale su suna more rayuwarsu yadda suke so, su ɗauka wannan falala ko alheri Ubangiji yake yi musu; Allah ya yi musu haka ne don su ƙara ɗaukar wa kawunansu wasu tarin laifuka, sannan za su fuskanci azaba mai wulaƙantarwa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, ba ya daga cikin hikimarsa ya ƙyale muminai da munafuƙai su ci gaba da zama a gauraye, ba tare da ya ware kowanne daga cikinsu ba. Dole ne a sami jarrabawa iri-iri wadda ta hanyarta ne za a gane mumini na gaskiya, kuma a gane munafuƙi.
Hakanan ba ya daga cikin hikimar Allah, ya bayyana wa wani abin da yake cikin zukatan bayinsa, har ya iya gane muminai da munafuƙai; sai dai Allah ya kawo wata jarrabawa wadda ta hanyarta ne zai bambance tsakanin mumini da munafuƙi. Amma duk da haka Allah yakan zabi wasu manzanni nasa ya sanar da su wani gaibu da izininsa da yardarsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su ƙara tabbata a kan imani da Allah da manzanninsa, ya kuma yi musu alƙawarin idan har sun yi hakan, to suna da wani lada mai girma.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da Annabinsa (ﷺ), da cewa, waɗanda suke rowa da dukiyar da Allah ya ba su daga falalarsa, kada su yi tsammani wannan rowar alheri ne gare su; a'a, sharri ne gare su, domin Allah ya yi musu tanadin azaba mai tsanani, wadda a lahira zai mayar musu da wannan dukiyar wani saƙandami, watau abin wuya na wutar Jahannama da zai rataya musu a wuyoyinsu, a yi ta yi musu azaba da shi ba ƙaƙƙautawa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, sammai da ƙasa duk nasa ne, don haka duk abin da halittunsa suka mallaka zai koma gare shi ne bayan sun halaka, shi zai gaje shi, kuma Allah yana da cikakken sanin bayinsa, kuma zai saka wa kowa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Duk wanda Allah ya ba shi dukiya bai fitar da zakka ba, to ranar alƙiyama za a mayar da wannan dukiyar wani tsohon kumurci mai koɗaɗɗen kai da ɗigon baƙi a idanunsa, a rataya masa shi, ya riƙa fincikar haɓarsa yana cewa: "Ni ne dukiyarka, ni ne ajiyayyar taskarka." Sannan Annabi (ﷺ) ya karanta faɗar Allah: "Kuma waɗanda suke yin rowa da abin da Allah ya ba su na falalarsa, kar su yi tsammanin hakan alheri ne a gare su…." [Bukhari #4565].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk abin da bayi suke yi na alheri ko na sharri ana rubutawa.

2. Duk wanda ya yarda da laifin mai laifi, to shi ma ya zama mai laifi. Shi ya sa Allah yake jingina wa Yahudawan zamanin Annabi (ﷺ) laifin iyayensu, domin sun yarda da wannan laifin.

3. Karyata gaskiya da yi wa Allah ƙarya wata siffa ce ta Yahudawa.

Suratu Ali-Imran (181-184)

لَّقَدْ سَمِعَ ٱللَّهُ قَوْلَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ فَقِيرٞ وَنَحۡنُ أَغۡنِيَآءُۘ سَنَكۡتُبُ مَا قَالُواْ وَقَتۡلَهُمُ ٱلۡأَنۢبِيَآءَ بِغَيۡرِ حَقّٖ وَنَقُولُ ذُوقُواْ عَذَابَ ٱلۡحَرِيقِ ١٨١
ذَٰلِكَ بِمَا قَدَّمَتۡ أَيۡدِيكُمۡ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَيۡسَ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ١٨٢ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ عَهِدَ إِلَيۡنَآ أَلَّا نُؤۡمِنَ لِرَسُولٍ حَتَّىٰ يَأۡتِيَنَا بِقُرۡبَانٖ تَأۡكُلُهُ

ٱلنَّارُ ۗ قُلْ قَدْ جَآءَكُمْ رُسُلٌ مِّن قَبْلِى بِٱلْبَيِّنَٰتِ وَبِٱلَّذِى قُلْتُمْ فَلِمَ قَتَلْتُمُوهُمْ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿١٨٣﴾ فَإِن كَذَّبُوكَ فَقَدْ كُذِّبَ رُسُلٌ مِّن قَبْلِكَ جَآءُو بِٱلْبَيِّنَٰتِ وَٱلزُّبُرِ وَٱلْكِتَٰبِ ٱلْمُنِيرِ ﴿١٨٤﴾

181. Tabbas haƙiƙa Allah ya ji maganar waɗannan da suka ce: “Lalle Allah mataulaci ne, mu ne mawadata.” Da sannu za Mu rubuta abin da suka faɗa, da kuma kisan da suka dinga yi wa annabawa ba tare da wani haƙƙi ba, kuma za Mu ce: “Ku ɗanɗani azaba mai ƙuna.

182. “Wannan kuwa, saboda abin da hannayenku suka gabatar ne, kuma lalle Allah ba mai zaluntar bayinsa ne ba.”

183. Su ne waɗanda suka ce: “Lalle Allah Ya yi alƙawari da mu kar mu yarda da kowane manzo har sai ya zo mana da wata sadaka wadda wuta za ta cinye ta.” Ka ce: “Haƙiƙa manzanni sun zo muku tun kafin ni, da hujjoji da kuma abin da kuka ce ɗin, to don me kuka kashe su in kun kasance masu gaskiya?”

184. To idan sun ƙaryata ka, to haƙiƙa an ƙaryata manzanni kafinka, waɗanda suka zo da hujjoji da littattafai da Littafi mai haskakawa.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin cewa, ya ji irin rashin kunyar da Yahudawa suka yi wa Allah suna cewa, wai Allah shi ne matalauci, su kuma mawadata ne. Allah ya tabbatar musu cewa, zai rubuta waɗannan miyagun maganganu nasu, har ma da ta’asar da suka yi ta kashe annabawa ba da wani haƙƙi ba, sannan ranar alƙiyama zai ce musu: Ku ɗanɗani azabar wuta mai ƙuna, saboda laifukan da kuka aikata a duniya, kuma Allah ba mai zaluntar bayinsa ne ba.
Dalilin saukar wannan ayar shi ne, kamar yadda Ibn Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ruwaito cewa: Wata rana Abubakar (Allah ya kara masa yarda) ya ce wa wani babban malamin Yahudawa, mai suna Finhasu, cewa: “Ka ji tsoron Allah ka musulunta. Wallahi ka san cewa, Annabi (ﷺ) Manzo ne daga Allah, ya zo muku da gaskiya daga gare shi, kuma kun karanta siffofinsa a cikin Littafin Attaura da Linjila.” Sai Finhasu ya ce: “Ya Ababakar, mu fa ba mu da wata buƙata a wurin Allah, shi ne ma yake da buƙata a wurinmu, kuma mu ba ma marairaice masa, kamar yadda shi yake marairaice mana. Mu mun wadatu, ba mu da wata buƙata a wurinsa, kuma shi ma da ya wadatu, ba shi da wata buƙata a wurinmu, to da bai karɓi rance a wurinmu ba, kamar yadda mutumin naku yake riyawa. Shi ya hana ku ci riba, shi kuma yana ba mu, da ba ya da buƙatarmu, da bai ba mu riba ba.” Sai Sayyidina Abubakar ya fusata, har ya mari Finhasu, sai Finhasu ya je ya faɗa wa Manzon Allah (ﷺ) cewa, Abubakar ya mare shi. Sai Annabi (ﷺ) ya tambayi Abubakar, me ya sa ya yi haka? Sai Abubakar ya faɗa masa duk abin da ya faru. Sai Finhasu ya musanta, ya ce shi bai faɗi haka ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar: “Tabbas haƙiƙa, Allah ya ji maganar waɗanda suka ce lalle Allah matalauci ne, mu ne mawadata....” [Aɗ-Ɗabari 7:441].
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fallasa wata ƙaryar ta Yahudawa, wadda suka yi da’awar cewa, Allah ya yi musu wasiyya da kada su yi imani da wani Manzo har sai ya zo musu da wata sadaka wadda wuta za ta zo ta cinye ta a gabansu suna gani, sannan ne za su yarda shi Manzon Allah ne, su yi imani da shi. Sai Allah ya umarci Annabinsa ya mayar musu martani da cewa, ai akwai manzanni da yawa a gabaninsu, waɗanda suka zaike wa jama’arsu suna ɗauke da mu’ujizoji da dama, waɗanda suka haɗa har da irin wannan mu’ujizar da suka nema, to amma sai ba su yi imani ba. Hasali ma kashe wasu annabawan suka yi. To don me suka kashe su, in har da gaske suke cewa, Allah ya umarce su da kada su yi imani sai da wanda ya zo musu da irin wannan mu’ujizar?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Annabinsa da kada ya damu don ƙaryatawar da waɗannan Yahudawan suke yi masa, domin ba shi ne farau ba; manzanni da dama da suka gabace shi, sun zo da

mu’ujizoji da littattafai da aka saukar musu, waɗanda ke ɗauke da wa’azuzzuka da nasihu masu ratsa zukata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a kan yawaita aikata ayyukan alheri kafin zuwan ajali, saboda babu wanda ya san lokacin mutuwarsa.

2. Nuna ƙasƙancin duniya da rashin tabbas ɗinta, domin duk wani abin jin daɗi da yake cikinta mai gushewa ne. Don haka bai kamata ta ruɗi mai hankali ba.

3. Ya kamata mumini ya sani cewa, duk irin yanayin da yake ciki, mai daɗi ko marar daɗi, wata jarrabawa ce daga Allah, domin ya ga godiyarsa ko haƙurinsa, ko kuma rashinsu.

4. Allah ya ba muminai labarin abin da za su riƙa gani daga magabtansu, Ma’abota Littafi da mushirikai, na cutarwa mai yawa, domin wasu hikimomi kamar haka:
• Don a tantance Musulmi na ƙwarai da lalatacce.
• Don Allah ya ɗaukaka darajar muminai da wannan ya kuma kankare musu laifuffukansu.
• Don imaninsu ya ƙaru yayin da suka ga aukuwar abin da Allah ya ba su labarinsa.
• Don su shirya wa faruwar hakan.
• Don idan ya faru su yi haƙuri, su jure.

Suratu Ali-Imran (185-186)

كُلُّ نَفۡسٖ ذَآئِقَةُ ٱلۡمَوۡتِۗ وَإِنَّمَا تُوَفَّوۡنَ أُجُورَكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۖ فَمَن زُحۡزِحَ عَنِ ٱلنَّارِ وَأُدۡخِلَ ٱلۡجَنَّةَ فَقَدۡ فَازَۗ وَمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَآ إِلَّا مَتَٰعُ ٱلۡغُرُورِ ١٨٥ لَتُبۡلَوُنَّ فِيٓ أَمۡوَٰلِكُمۡ وَأَنفُسِكُمۡ وَلَتَسۡمَعُنَّ مِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِكُمۡ وَمِنَ ٱلَّذِينَ أَشۡرَكُوٓاْ أَذٗى كَثِيرٗاۚ وَإِن تَصۡبِرُواْ وَتَتَّقُواْ فَإِنَّ ذَٰلِكَ مِنۡ عَزۡمِ ٱلۡأُمُورِ ١٨٦

185. Kowane rai zai ɗanɗani mutuwa. Kuma a ranar alƙiyama ne za a cika muku ladan ayyukanku; to duk wanda aka nisanta shi daga wuta, kuma aka shigar da shi Aljanna, to haƙiƙa ya rabauta. Kuma rayuwar duniya ba komai ba ce face jin daɗi mai ruɗarwa.

186. Lalle za a jarrabe ku a cikin dukiyoyinku da rayukanku, kuma lalle za ku riƙa jin cutarwa mai yawa daga waɗanda aka bai wa Littafi kafinku, haka kuma daga waɗanda suke mushirikai. Amma idan har kuka yi haƙuri, kuma kuka tsare dokar Allah, to lalle wannan yana daga cikin manyan al’amura.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, kowane rai dole ne sai ya mutu, kuma Allah ne ke yi wa kowa cikakken sakamako na aikinsa ranar gobe ƙiyama. To duk wanda aka tserar da shi daga shiga wuta, sannan aka shigar da shi Aljanna, to haƙiƙa wannan mutum ya rabauta. Kuma rayuwar duniya wani ɗan jin daɗi ne ƙanƙani, mai gushewa da gaggawa bayan ya ruɗi ma’abocinsa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle gurbin bulala a Aljanna ya fi duniya da abin da yake cikinta. Ku karanta wannan ayar in kun ga dama: “To duk wanda aka nisanta shi daga wuta, kuma aka shigar da shi Aljanna, to haƙiƙa ya rabauta, kuma rayuwar duniya ba komai ba ce, face ɗan jin daɗi mai ruɗarwa.” [Tirmizi #3013, da Nasa’i, As-Sunan *Alkubra* #11085].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa muminai cewa za a jarrabe su da aukawar masifu a dukiyoyinsu, ta hanyar lalacewarsu ko hasarar kasuwanci, kuma za a jarrabe su a rayukansu, ta hanyar mutuwa ko kisa ko samun raunuka ko rashin lafiya. Sannan kuma za su dinga jin maganganu na cutarwa da gallazawa daga maƙiyansu waɗanda aka ba wa Littafi gabaninsu, wato Yahudawa da Nasara, da kuma mushirikai, saboda za su riƙa zagin su, suna sukar addininsu, suna jifar su da tuhumce-tuhumce iri-iri da yin izgili ga shari'arsu. To amma idan sun yi haƙuri a kan hakan, kuma suka kiyaye dokokin Allah, to yin hakan yana daga cikin manyan al'amura da suke buƙatar juriya da himma.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin bayyana ilimi a kan masu ilimi ta duk hanyar da ta dace.

2. Sukan masu son a yaba musu a kan aikin da ba nasu ba.

3. Babu laifi a yaba wa mutum a kan aikin da ya yi na alheri, don ƙarfafa masa gwiwa, idan kuma babu jin tsoron girman kai ya shige shi.

4. Babu laifi mutum ya yi farin ciki a kan yabonsa da aka yi bisa wani aikin alheri, matuƙar ba ya yi ne domin riya ba, kuma bai yarda jiji da kai ya kama shi ba.

Suratu Ali-Imran (187-188)

وَإِذۡ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ لَتُبَيِّنُنَّهُۥ لِلنَّاسِ وَلَا تَكۡتُمُونَهُۥ فَنَبَذُوهُ وَرَآءَ ظُهُورِهِمۡ وَٱشۡتَرَوۡاْ بِهِۦ ثَمَنٗا قَلِيلٗاۖ فَبِئۡسَ مَا يَشۡتَرُونَ ١٨٧ لَا تَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ يَفۡرَحُونَ بِمَآ أَتَواْ وَّيُحِبُّونَ أَن يُحۡمَدُواْ بِمَا لَمۡ يَفۡعَلُواْ فَلَا تَحۡسَبَنَّهُم بِمَفَازَةٖ مِّنَ ٱلۡعَذَابِۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١٨٨

187. Kuma ka tuna lokacin da Allah Ya ɗauki alƙawari daga waɗanda aka bai wa Littafi cewa: "Lalle ku bayyana shi ga mutane, kuma kada ku ɓoye shi." Sai suka jefar da shi can bayansu, kuma suka musanya shi da wani ɗan farashi ƙanƙani. To tir da abin da suke yin musanye da shi.

188. Kada ka yi tsammanin waɗanda suke yin farin ciki da irin abin da suka aikata, kuma suna son a riƙa yabon su da abin da ba su aikata ba, to kada ka yi tsammanin za su tsira daga azaba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tuna wa Annabinsa (ﷺ) wani mummunan aiki na Yahudawa da Nasara, lokacin da Allah ya yi ƙaƙƙarfan alƙawari da su na cewa, za su fito su bayyana wa mutane abin da yake cikin littattafan da aka saukar wa annabawansu, kuma ba za su ɓoye komai daga ciki ba. Daga ciki kuwa har da siffofin Annabi (ﷺ) da suka zo a Attaura da Linjila; to amma sai suka saba wannan alƙawari, suka ɓoye waɗannan siffofin Annabi (ﷺ), ba don komai ba, sai don ɗan abin da za su samu na duniya. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir da irin wannan aiki nasu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Duk wanda aka yi masa tambaya ta ilimi, sannan ya ɓoye, to za a sa masa linzamin wuta ranar gobe ƙiyama." [Abu Dawud #3658, da Tirmizi #2649, da Ibnu Maja #266].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, kada ya yi zaton mutanen da suke farin ciki da miyagun ayyukan da suka yi na ɓoye ilimin da Allah ya ba su, kuma suke son a riƙa yaba musu a kan aikin da ba su yi ba, kada ya yi zaton waɗannan mutane za su tsira daga azabar Allah ranar alƙiyama; tabbas suna da wata azaba mai raɗaɗi.

An karɓo daga Abu Sa'id Alkhudri (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Wasu munafuƙai duk sanda Annabi (ﷺ) ya fita yaƙi, sai su noƙe su ƙi fita tare da shi, kuma su riƙa farin ciki da hakan. Idan Annabi (ﷺ) ya dawo daga yaƙi, sai su je suna rantsuwa, suna faɗar hanzari na ƙarya, sannan kuma su riƙa son a yabe su da aikin da ba su yi ba, sai wannan ayar ta sauka: "Kada ku yi tsammanin waɗanda suke farin ciki da abin da suka yi, kuma suna son a riƙa yabon su da abin da ba su aikata ba...." [Bukhari #4567, da Muslim #2777].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga yin tunani game da halittar sammai da ƙasa, saboda abubuwan da suka ƙunsa na manyan dalilai masu tabbatar da Ɗayantakar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai.

2. Tunani da duba cikin halittar sammai da ƙasa yana ƙara wa bawa imani da yaƙini.

3. Duk sa'adda mutum ya zama mai zurfin hankali, to saninsa ga Allah da ayoyinsa za su ƙara haɓaka.

4. Halaccin yin tawassuli da siffofin Allah da ayyuka na ƙwarai, kamar imani da Allah da Manzonsa (ﷺ).

5. Yana daga cikin ladubban addu'a, mutum ya yawaita yabo da kirari ga Allah Ta'ala.6. Babu wani bambanci tsakanin namiji da mace wajen sakamakon ayyukan ibada da kusanci zuwa ga Allah. Duk wanda ya yi aiki nagari, Allah zai yi masa sakayya da kyakkyawan sakamako, ba tare da la'akari da bambancin jinsi ba.

Suratu Ali-Imran (189-195)

لَا تَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ يَفۡرَحُونَ بِمَآ أَتَواْ وَّيُحِبُّونَ أَن يُحۡمَدُواْ بِمَا لَمۡ يَفۡعَلُواْ فَلَا تَحۡسَبَنَّهُم بِمَفَازَةٖ مِّنَ ٱلۡعَذَابِۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١٨٨ وَلِلَّهِ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ١٨٩ إِنَّ فِي خَلۡقِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَٱخۡتِلَٰفِ ٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ لَأٓيَٰتٖ لِّأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ١٩٠ ٱلَّذِينَ يَذۡكُرُونَ ٱللَّهَ قِيَٰمٗا وَقُعُودٗا وَعَلَىٰ جُنُوبِهِمۡ وَيَتَفَكَّرُونَ فِي خَلۡقِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ رَبَّنَا مَا خَلَقۡتَ هَٰذَا بَٰطِلٗا سُبۡحَٰنَكَ فَقِنَا عَذَابَ ٱلنَّارِ ١٩١ رَبَّنَآ إِنَّكَ مَن تُدۡخِلِ ٱلنَّارَ فَقَدۡ أَخۡزَيۡتَهُۥۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ أَنصَارٖ ١٩٢ رَّبَّنَآ إِنَّنَا سَمِعۡنَا مُنَادِيٗا يُنَادِي لِلۡإِيمَٰنِ أَنۡ ءَامِنُواْ بِرَبِّكُمۡ فَـَٔامَنَّاۚ رَبَّنَا فَٱغۡفِرۡ لَنَا ذُنُوبَنَا وَكَفِّرۡ عَنَّا سَيِّـَٔاتِنَا وَتَوَفَّنَا مَعَ ٱلۡأَبۡرَارِ ١٩٣ رَبَّنَا وَءَاتِنَا مَا وَعَدتَّنَا عَلَىٰ رُسُلِكَ وَلَا تُخۡزِنَا يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ إِنَّكَ لَا تُخۡلِفُ ٱلۡمِيعَادَ ١٩٤ فَٱسۡتَجَابَ لَهُمۡ رَبُّهُمۡ أَنِّي لَآ أُضِيعُ عَمَلَ عَٰمِلٖ مِّنكُم مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰۖ بَعۡضُكُم مِّنۢ بَعۡضٖۖ فَٱلَّذِينَ هَاجَرُواْ وَأُخۡرِجُواْ مِن دِيَٰرِهِمۡ وَأُوذُواْ فِي سَبِيلِي وَقَٰتَلُواْ وَقُتِلُواْ لَأُكَفِّرَنَّ عَنۡهُمۡ سَيِّـَٔاتِهِمۡ وَلَأُدۡخِلَنَّهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ ثَوَابٗا مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عِندَهُۥ حُسۡنُ ٱلثَّوَابِ ١٩٥

189. Kuma ga Allah ne mulkin sammai da ƙasa yake. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai.

190. Lalle a cikin halittar sammai da ƙasa da sassaɓawar dare da rana, tabbas akwai ayoyi ga ma'abota hankula.

191. Su ne waɗanda suke ambaton Allah a tsaye da kuma zaune da kuma kishingiɗe, suna kuma tunani a kan halittar sammai da ƙasa, (suna cewa): “Ya Ubangijinmu, ba Ka halicci wannan a banza ba, tsarki ya tabbata gare Ka, Ka tserar da mu daga azabar wuta.

192. “Ya Ubangijinmu, lalle duk wanda Ka shigar da shi wuta, to haƙiƙa Ka kunyata shi; kuma azzalumai ba su da mai taimakon su.

193. “Ya Ubangijinmu, lalle mu mun ji wani mai kira yana yin kira zuwa imani cewa: “Ku yi imani da Ubangijinku;” sai muka yi imani. Ya Ubangijinmu, Ka gafarta mana zunubanmu, kuma Ka kankare mana kurakuranmu, kuma Ka karɓi rayukanmu tare da mutane masu ɗa’a.

194. “Ya Ubangijinmu, kuma Ka ba mu abin da Ka yi mana alƙawari da shi ta harshen manzanninka, kuma kada Ka kunyatar da mu ranar alƙiyama. Lalle Kai ba Ka saɓa alƙawari.”

195. Sai Ubangijinsu Ya amsa musu (cewa): “Lalle Ni ba zan tozarta aikin wani mai aiki daga cikinku ba, namiji ne ko mace; sashinku yana tare da sashe. To waɗanda suka yi hijira kuma aka fitar da su daga gidajensu kuma aka cutar da su wajen bin tafarkina kuma suka yi yaƙi kuma aka kashe su, lalle zan kankare musu kurakuransu, kuma lalle zan shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Wannan lada ne daga wajen Allah, kuma a wurin Allah ne mafi kyawun lada yake.”

A cikin waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, shi kaɗai ne mai mulkin sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu, kuma shi ne mai cikakken iko a kan komai. Sannan ya sanar da cewa, a cikin halittar sammai da ƙasa da abubuwan da suka ƙunsa da cancanzawar dare da rana, wannan ya zo, wannan ya tafi, lalle akwai manya-manyan ayoyi da dalilai ga masu lafiyayyen hankali, da suke tabbatar da samuwar Mahalicci da siffofinsa. Waɗannan kuwa su ne masu ambaton Allah koyaushe, a cikin kowane yanayi, a tsaye suke ko a zaune ko a kwance. Suna tunani game da halittar sammai da ƙasa, suna cewa: “Ya Ubangijinmu, mun yi imani ba ka yi wannan halittar a banza ba; ka tsarkaka daga yin wannan, don haka ka tsare mu daga azabar wuta; duk kuwa wanda ka saka shi cikinta, to tabbas ka tozartar da shi, kuma azzalumai ba su da masu taimaka musu.” Suka ci gaba da cewa: “Ya Ubangijinmu, mun ji Annabinka yana kira zuwa ga yin imani da kai, kuma mun amsa kiransa, mun yi imani, don haka ka gafarta mana laifukanmu, kuma ka kankakre mana munanan ayyukanmu, kuma ka karɓi rayukanmu tare da mutanen kirki. Ya Ubangijinmu, alƙawarin da ka yi ta harshen manzanninka, na ba mu kyakkyawan sakamako ka zartar da shi, kada kuma ka kunyata mu a ranar alƙiyama a gaban halittunka; lalle mun tabbatar ba ka saɓa alƙawari.”
Sai ko Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya karɓi wannan roƙo nasu, kuma ya yi alƙawarin ba zai taɓa tozarta aikin mai aiki ba, namiji ne shi ko mace ce. Don haka waɗanda suka baro garuruwansu na kafirci ko kuma kafirai suka koro su, aka cutar da su saboda sun riƙe gaskiya, sun yi imani da Allah da Manzonsa, suka kuma yi yaƙi don Allah, kuma aka kashe su, to waɗannan Allah zai kankare musu laifukansu, kuma zai saka su gidajen Aljanna, waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu; wannan babban sakamako ne a gare su, saboda ƙoƙarin da suka yi na aikin alheri a duniya. Allah shi ne mai kyakkyawan sakamako ga duk wanda ya yi aikin ƙwarai; zai saka masa da abin da ido bai taɓa gani ba, kunne bai taɓa ji ba, zuciyar wani ɗan’adam ba ta taɓa tunaninsa ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Wani dare na kwana a ɗakin Maimuna uwar muminai (Allah ya kara mata yarda), kuma a ranar Annabi (ﷺ) yana ɗakinta, domin in ga yadda yake sallarsa ta dare. Annabi (ﷺ) ya yi hira da iyalinsa na wani ɗan lokaci, sannan ya kwanta ya yi barci. A sulusin ƙarshe na dare, sai ya tashi zaune, ya ɗaga kai sama, sai ya karanta wannan aya (aya ta 190), sannan ya tashi ya yi alwala, ya yi asiwaki, sannan ya yi salla raka’a goma sha ɗaya, sannan Bilal ya

kira sallar Asuba. Sai Annabi (ﷺ) ya sallaci raka'a biyu, sannan ya fita ya jagoranci sallar Asuba. [Bukhari #7452].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hani ga Musulmi da kar ya ruɗu da irin ni'ima da jin daɗi da kafirai suke mora; wannan ɗan wani abu ne ƙanƙani, kuma mai gushewa da gaggawa.

2. Samun arziki da jin daɗin duniya ba shi yake nuna yardar Allah da soyayyarsa ga wanda ya wa baiwar ba. Ma'aunin yarda da soyayyar Allah ita ce yi wa Allah da Manzonsa (ﷺ) ɗa'a.

3. Babu wata hanyar samun rabo daga Allah, sai ta yin haƙuri da juriya da jajircewa da kuma biyayya ga Allah da taimakon addininsa.

4. Addinin Musulunci ya tattara ne a kan abubuwa guda uku: Aikata abin da aka yi umarni da shi da barin abin da aka hana da kuma haƙuri a kan abin da Allah ya ƙaddara faruwarsa.

Suratu Ali-Imran (196-200)

لَا يَغُرَّنَّكَ تَقَلُّبُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي ٱلۡبِلَٰدِ ١٩٦ مَتَٰعٞ قَلِيلٞ ثُمَّ مَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۚ وَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ١٩٧ لَٰكِنِ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ رَبَّهُمۡ لَهُمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي
مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا نُزُلٗا مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِۗ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ خَيۡرٞ لِّلۡأَبۡرَارِ ١٩٨ وَإِنَّ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ لَمَن يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكُمۡ
وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِمۡ خَٰشِعِينَ لِلَّهِ لَا يَشۡتَرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ ثَمَنٗا قَلِيلًاۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ أَجۡرُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٩٩ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ ٱصۡبِرُواْ وَصَابِرُواْ وَرَابِطُواْ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٢٠٠

196. Kada zirga-zirgar kafirai a cikin garuruwa ta ruɗe ka.

197. Wani ɗan jin daɗi ne ƙanƙani, sannan makomarsu Jahannama. Kuma tir da wannan shimfiɗar.

198. Amma waɗanda suka bi dokokin Ubangijinsu suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su dawwama a cikinsu, wannan liyafa ce ta musamman daga wajen Allah. Kuma abin da yake wajen Allah shi ne mafi alheri ga masu biyayya.

199. Kuma lalle a cikin Ma'abota Littafi, tabbas akwai waɗanda suke yin imani da Allah da kuma abin da aka saukar muku da kuma abin da aka saukar musu, suna masu ƙaskantar da kai ga Allah, ba sa musanya ayoyin Allah da wani ɗan farashi ƙanƙani. Waɗannan suna da lada a wajen Ubangijinsu. Lalle Allah Mai gaggawar hisabi ne.

200. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi haƙuri, kuma ku jure matuƙa ga yin haƙuri, kuma ku tsare iyakokin ƙasa, kuma ku kiyaye dokokin Allah don ku sami rabauta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa Annabinsa (ﷺ) kashedi da ruɗuwa da kai-komon kafirai a duniya da tinƙahon da suke yi da bunƙasar harkar kasuwanci da ƙarfin tattalin arziki da ƙarfin sojoji. Duk waɗannan wani ɗan taƙaitaccen jin daɗi ne; nan da nan zai ƙare, sannan daga ƙarshe wutar jahannama ce makomarsu tir kuwa da irin wannan makoma.
To amma masu bin dokokin Ubangijinsu ta hanyar aikata abin da ya wajabta musu da barin abin da ya haramta musu; to an tanadar musu gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, kuma

su zauna cikinsu har abada. Wannan wata liyafa ce Allah ya shirya musu. Don haka abin da yake wurin Allah na kyakkyawan sakamako ga waɗanda suka bi shi, ya fi alheri fiye da wani ɗan gajeren jin daɗi na duniya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a cikin Ma'abota Littafi akwai waɗanda sun yi imani da Allah, suna kaɗaita shi da bauta, kuma sun yi imani da Manzonsa da Alƙur'anin da aka saukar masa da kuma littattafan da aka saukar musu, suna masu ƙasƙantar da kansu ga Allah, ba sa canza abin da yake cikin littattafansu, ba sa kuma ɓoye gaskiyar da take ciki, domin samun ɗan wani taƙaitaccen jin daɗi na duniya; to waɗannan suna da babban sakamako a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Lalle kuma Allah mai gaggawar sakamako ne.

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Lokacin da labarin rasuwar Najashi ta zo mana, Annabi (ﷺ) ya ce mana: "Ku yi masa salla." Sai sahabbai suka ce: "Yanzu ma yi wa wani bawa mutumin Habasha salla?" Sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Kuma lalle cikin ma'abota Littafi, tabbas akwai waɗanda suka yi imani da Allah da kuma abin da aka saukar muku da kuma abin da aka saukar musu, suna masu ƙasƙantar da kansu ga Allah." [An-Nasa'i, *As-Sunanul Kubra* #11088, da Bazzar #6556].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa muminai da yin haƙuri da kuma dauriya a kan rinjayar maƙiya addinin Allah, su jajirce har su ma su sami nasara a kan maƙiyansu kuma su tsare kan iyakokin da ake tsoron shigowar maƙiya daga gare su, sannan su kiyaye dokokin Allah, ta hanyar aikata umarninsa da barin haninsa; da wannan ne za su sami rabauta duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haƙƙin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sama da haƙƙin 'yan'uwantaka, domin shi ne mahaliccin kowa da komai.

2. Idan mutane sun fahimci cewa asalinsu duka ɗaya ne, watau daga Adamu da Hauwa'u, to wajabi ne su bar yi wa juna alfahari da asali ko dangantaka, su haɗu su girmama juna, su yi wa juna kyakkyawar mu'amala.

3. Sada zumunci babban abu ne, don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gwama shi da maganar taƙawa watau bin dokokin Allah. Duk mai taƙawa kuwa dole ne ya zama mai sada zumuncinsa.

4. Matar mutum tana da muhimmanci matuƙa a wurinsa, shi ya sa sanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai kuma ya halitta masa matarsa Hauwa'u, don nuna muhimmancin aure a rayuwar ɗan'adam.

5. Ayar tana tabbatar da cewa, asalin mutum shi ne Annabi Adamu da Hauwa'u, saɓanin abin da wasu kafirai suke riyawa wai asalinsa biri ne. Yarda da wannan maganar ma kafirci ne.

4-Suratun Nisa'i

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da sunan *Suratun Nisa'i'*.
An karɓo daga Ma'adan ɗan Abu Ɗalha Al-Ya'amuri ya ce: Wata rana Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) ya yi huɗuba a ranar Juma'a, ya ambaci Annabin Allah ya kuma ambaci Abubakar, sannan ya ce: "Ba zan bar wani abu mai muhimmanci a bayana ba kamar batun hukuncin *Kalala*. Ban matsa wa Annabi (ﷺ) da tambaya a kan wani abu ba kamar yadda na matsa masa game da sha'anin *Kalala*, shi kuma bai kausasa mini a komai ba kamar yadda ya kausasa mini a kan wannan batun, har sai da ta kai ya zungure ni da ɗan yatsansa a ƙirjina, ya ce: " Ya Umar ashe yanzu ayar da ke ƙarshen *Suratun Nisa'i* ba ta ishe ka ba? Idan kuma na ƙara tsawon rai to zai yi bayanin hukuncin *Kalala* wanda makarancin Alƙur'ani da wanda ma ba makarancinsa ba zai yi hukunci da shi." [Muslim #1617].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa Sura ce *Madaniyya*. Hadisin Nana A'isha yana ƙara tabbatar da haka, domin tana cewa: " *'Suratul* Baƙara' da *'Suratun Nisa*'i' sun sauka lokacin da nake tare da Annabi (ﷺ)." [Bukhari #4993]. Babu saɓani a tsakanin malamai cewa A'isha (Allah ya ƙara masa yarda) ta tare ne a Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce ta tis'in da uku (93) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan *'Suratul Mumtahana', kafin 'Suratuz Zalzalah*'.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Madina da Makka da Basra ayoyinta ɗari da saba'in da biyar ne (175). A wurin mutanen Kufa kuwa ayoyinta ɗari da saba'in da shida ne (176). Sannan a wurin mutanen Sham tana da ayoyi ɗari da saba'in da bakwai (177).

5. Babban Jigonta:
• Ba da mahimmanci ga Tauhidi da al'amuran da suka shafi imani da mayar da martani a kan miyagun aƙidu da kafa hujjoji a kan ingancin annabcin Manzon Allah (ﷺ) tare da gargaɗi game da munafukai.
• Kulawa da sha'anin iyali da tsara zamantakewar aure da alaƙa tsakanin ma'aurata da bayanin haƙƙoƙin dangi na jini da bayanin rabon gado.
• Ba da muhimmanci a kan bayanin rukunan kafuwar daula da abubuwan da ake buƙata domin ɗorewarta, da kuma magana a kan jihadi don ɗaukaka kalmar Allah.
• Bayar da mahimmanci a kan tsare rayuka da hukunce-hukuncen kisan kai da tsare dukiyoyi da kula da haƙƙin mutane.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Magana a kan hukunce-hukuncen da suka shafi mata da bayanin wasu daga cikin haƙƙoƙinsu.

• Tsara da yawa daga cikin alaƙar mace da mijinta, daga ciki akwai batun shugabancin miji a gidansa da halaccin auren mace fiye da ɗaya da zancen gado da sadaki da saki da shayarwa da abin da ya danganci hakan.
• Surar ta taɓo magana a kan rantsuwa da hukunce-hukuncenta.
• Magana a kan haƙƙoƙin marayu da yadda ya kamata a yi taʾammali da dukiyar maraya.
• Game da abin da kuwa ya shafi dukiya, Surar ta yi magana a kan haramcin cin dukiyar wani ba da haƙƙi ba da kwaɗaitarwa a kan ciyarwa don Allah da gargaɗìn masu rowa suna kuma umarni da yin rowa.
• Surar ta yi magana a kan wasu hukunce-hukuncen fiƙihu masu yawa, kamar hukuncin salla a cikin maye da wajabcin wankan janaba da hukuncin taimama da sauransu.
• Surar har ila yau ta yi magana sosai a kan maʾabota littafi da bayanin ɓatan da suke a kai da kuma yawan warware alƙawuran da suke yi da yadda Allah ya laʾance su ya yi hushi da su da muguwar muʾamalarsu ga annabawa, da sauran abubuwa da suka danganci haka.
• Surar ta taɓo batu a kan hukunci a Musulunci da irin hukuncin da ya wajaba daular Musulunci ta tsayar na adalci da wajabcin bin Allah da Manzonsa da shugabanni da kuma bayanin abin da za a riƙe yayin jayayya domin raba gardama.
• Ta yi magana a kan munafukai da tona musu asiri da mummunan sakamakonsu a lahira.

Suratun Nisa’i (1)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُواْ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى خَلَقَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ وَخَلَقَ مِنْهَا زَوْجَهَا وَبَثَّ مِنْهُمَا رِجَالًا كَثِيرًا وَنِسَآءً ۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِى تَسَآءَلُونَ بِهِۦ وَٱلْأَرْحَامَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَيْكُمْ رَقِيبًا ﴿١﴾

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya ku mutane, ku kiyaye dokokin Ubangijinku Wanda Ya halicce ku daga rai guda ɗaya, kuma Ya halicci matarsa daga shi, kuma Ya yaɗa maza da mata masu yawa daga gare su. Kuma ku kiyaye dokokin Allah Wanda kuke yi wa juna magiya da Shi, kuma ku kiyaye (yanke) zumunci. Lalle Allah Mai kula da ku ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da umartar mutane gaba ɗaya da su ji tsoron Ubangijinsu, su kiyaye dokokin da ya gindaya musu a Littafinsa mai tsarki, ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da shi da barin abin da ya hana, domin shi ne mahaliccinsu, mamallakinsu, wanda yake kula da rayuwarsu. Ya halicce su ne gaba ɗayansu daga rai guda ɗaya, shi ne Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kuma daga wannan rai ya halicci abokiyar haɗinsa, wato Hauwa’u; ta hanyarsu kuma ya yaɗa mutane masu yawa maza da mata a bayan ƙasa. Ya sake umartar su kuma da su kiyaye dokokin Allah wanda da sunansa ne suke yi wa juna magiya, sannan su kula da haƙƙin sada zumunci, kada su yanke shi, domin shi ma yana da girma a wurin Allah, Allah kuma yana ganin duk ayyukansu, kuma zai saka musu a kansu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce; “Ku yi wasiyya da kulawa da mata, domin mace an halicce ta ne daga ƙashin haƙarƙari, kuma inda ya fi tanƙwara a haƙarƙari shi ne na samansa; idan ka ce sai ka miƙar da shi, to za ka karya shi, idan ka ƙyale shi, to zai ci gaba da zama a tanƙware, don haka ku yi wasiyyar kula da mata.” [Bukhari #3331, da Muslim #1468].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman sha’anin marayu.

2. Mutum ya zama mai taka-tsantsan ko da yaushe domin kauce wa faɗawa cikin haramun.

3. Duk abin da zai kai mutum ga auka wa haramun, to wajibi ne ya guje shi, ko da kuwa wannan abu halal ne a karan-kansa.

4. Halaccin auren mata biyu zuwa huɗu ga wanda zai yi adalci a tsakaninsu.

5. Sadaki na matar da aka aura ne, bai halatta waliyyinta ya ƙwace mata shi ba, sai abin da ta ba shi cikin daɗin rai.

6. Wajibi ne ga waɗanda suke kula da dukiyoyin marayu su alkinta musu su kamar irin yadda suke alkinta tasu dukiyar, ko fiye.

Suratun Nisa'i (2-6)

وَءَاتُواْ ٱلۡيَتَٰمَىٰٓ أَمۡوَٰلَهُمۡۖ وَلَا تَتَبَدَّلُواْ ٱلۡخَبِيثَ بِٱلطَّيِّبِۖ وَلَا تَأۡكُلُوٓاْ أَمۡوَٰلَهُمۡ إِلَىٰٓ أَمۡوَٰلِكُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ حُوبٗا كَبِيرٗا ۝٢ وَإِنۡ خِفۡتُمۡ أَلَّا تُقۡسِطُواْ فِي ٱلۡيَتَٰمَىٰ فَٱنكِحُواْ مَا طَابَ لَكُم مِّنَ ٱلنِّسَآءِ مَثۡنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَۖ فَإِنۡ خِفۡتُمۡ أَلَّا تَعۡدِلُواْ فَوَٰحِدَةً أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُمۡۚ ذَٰلِكَ أَدۡنَىٰٓ أَلَّا تَعُولُواْ ۝٣ وَءَاتُواْ ٱلنِّسَآءَ صَدُقَٰتِهِنَّ نِحۡلَةٗۚ فَإِن طِبۡنَ لَكُمۡ عَن شَيۡءٖ مِّنۡهُ نَفۡسٗا فَكُلُوهُ هَنِيٓـٔٗا مَّرِيٓـٔٗا ۝٤ وَلَا تُؤۡتُواْ ٱلسُّفَهَآءَ أَمۡوَٰلَكُمُ ٱلَّتِي جَعَلَ ٱللَّهُ لَكُمۡ قِيَٰمٗا وَٱرۡزُقُوهُمۡ فِيهَا وَٱكۡسُوهُمۡ وَقُولُواْ لَهُمۡ قَوۡلٗا مَّعۡرُوفٗا ۝٥ وَٱبۡتَلُواْ ٱلۡيَتَٰمَىٰ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغُواْ ٱلنِّكَاحَ فَإِنۡ ءَانَسۡتُم مِّنۡهُمۡ رُشۡدٗا فَٱدۡفَعُوٓاْ إِلَيۡهِمۡ أَمۡوَٰلَهُمۡۖ وَلَا تَأۡكُلُوهَآ إِسۡرَافٗا وَبِدَارًا أَن يَكۡبَرُواْۚ وَمَن كَانَ غَنِيّٗا فَلۡيَسۡتَعۡفِفۡۖ وَمَن كَانَ فَقِيرٗا فَلۡيَأۡكُلۡ بِٱلۡمَعۡرُوفِۚ فَإِذَا دَفَعۡتُمۡ إِلَيۡهِمۡ أَمۡوَٰلَهُمۡ فَأَشۡهِدُواْ عَلَيۡهِمۡۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ حَسِيبٗا ۝٦

2. Kuma ku bai wa marayu dukiyoyinsu; kuma kada ku musanya kyakkyawa da mummuna; kuma kada ku ci dukiyoyinsu haɗe da dukiyoyinku. Lalle yin hakan ya tabbata zunubi ne mai girma.

3. Kuma idan kun ji tsoron cewa ba za ku iya yin adalci ba dangane da marayu, to ku auri matan da kuke so, ko dai bibbiyu ko uku-uku ko kuma hurhuɗu. To idan kun ji tsoron ba za ku iya yin adalci ba, to sai ku taƙaita a kan ɗaya ko kuma abin da kuka mallaka na ƙwarƙwarori. Hakan shi ya fi nisanta ku daga zalunci.

4. Kuma ku bai wa mata sadakinsu kyauta. Amma idan suka ba ku wani abu cikin daɗin rai, to ku ci shi yana mai daɗi da saukin haɗiya.

5. Kuma kada ku bai wa (marayu) wawaye dukiyoyinku wadda Allah Ya sanya rayuwarku take tsaye a kai, kuma ku ciyar da su, kuma ku tufatar da su daga cikinta, kuma ku faɗa musu magana mai daɗi.

6. Kuma ku jarraba hankulan marayu, har lokacin da suka isa aure, to idan kun ga alamar hankali tare da su, sai ku ba su dukiyoyinsu; kuma kada ku ci dukiyarsu ta hanyar almubazzaranci da kuma gaggawa don gudun kada su girma. Duk kuma wanda ya kasance mawadaci ne, to ya kame kansa; wanda kuma ya kasance mabuƙaci ne, to ya ci ta hanyar da ta dace. To idan za ku miƙa musu dukiyoyinsu, sai ku kafa musu shaidu. Kuma Allah Ya isa Mai hisabi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin haƙƙoƙin marayu da kulawa da dukiyoyinsu har lokacin da za su balaga su yi hankali. Maraya shi ne duk wani yaro ko yarinya da suka rasa iyayensu maza, sannan ba su balaga ba. 'Ya mace tana da buƙatar kulawa har ta sami mijin aure. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci waɗanda kula da marayu ta rataya a wuyansu da cewa, su mayar musu da dukiyarsu da take hannuwansu gaba ɗaya da zarar sun balaga, kuma an ga alamun hankali tare da su. Ya hana su cin dukiyar maraya ba da wani haƙƙi ba, ko su musanya da dukiyar maraya mai inganci da tasu marar inganci, don sun ga shi yaro ne ba zai iya fahimta ba. Hakanan ya haramta musu su haɗa

dukiyarsu da ta marayun da suke ƙarƙashinsu da niyyar su cinye musu ita ba bisa gaskiya ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce yin haka zalunci ne mai girma.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuma yi magana a kan wani abu da ya riƙa faruwa a lokacin jahiliyya, dangane da 'ya'ya mata marayu. Kamar mutum an bar masa wasiyyar wata marainiya da iyayenta suka bar mata dukiya mai yawa, sai wannan mutum saboda kwaɗayin dukiyarta, sai ya aure ta ba don yana son ta ba, sai don ya mallake mata dukiya, kamar yadda A'isha (Allah ya kara mata yarda) ta yi bayani [Dubi Bukhari #4573 da Muslim #3018]. Ko kuma mutumin da marainiya take ƙarƙashinsa, sai ya yi kwaɗayin aurenta saboda dukiyarta, amma kuma ba ya son ya ba ta cikakken sadakin da ya dace da ita, sai Allah ya hana shi ya aure ta har sai idan zai yi mata adalci ya ba ta cikakken sadakinta. [Dubi Bukhari #4575].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da cewa, idan ba za su iya adalci ga mata marayu da suke ƙarƙashinsu ba, ba za su iya ba su cikakken sadakinsu ba, ko kuma ba za su kula da haƙƙoƙinsu ba, to su je su auri wasu matan da zukatansu suka kwanta musu da su; suna iya auren mata biyu ko uku ko huɗu. Su ma idan sun ga ba za su iya yin adalci a tsakaninsu ba, to su tsaya a kan auren mace ɗaya, ko ma su taƙaita a kan ƙwarƙwarorinsu, domin su ƙwarƙwarori babu rabon kwana a tsakaninsu. Taƙaitawa a kan mace ɗaya ko ƙwarƙwara ya fi kusa da tabbatar da adalci da kauce wa zalunci.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga maza da su ba wa mata sadakin aurensu wanda Allah ya wajabta a ba su idan an aure su. To amma idan su matan ne suka bar musu wani abu daga sadakinsu a matsayin kyauta, don ganin damarsu ba tare da an matsa musu ba, to su karɓa su ci, babu wata matsala.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana lokacin da bai dace a ba wa maraya wawa marar nutsuwa dukiyarsa ba yayin da ya umarci masu kula da su cewa kada su bayar da dukiyarsu wadda Allah ya sanya a hannunsu ga wani maraya wanda bai san yadda ya kamata ya kula da ita ba, saboda ƙuruciya ko rashin wayo, ko wani dalili. Lalle su tsaya su kula musu da dukiyarsu kamar yadda suke kula da tasu. Kuma su ciyar da su, su shayar da su, su tufatar da su daga cikinta, sannan su faɗa musu magana mai daɗi yayin da suka nuna buƙatar a ba su dukiyarsu. Suna iya sanar da su cewa sai sun yi wayo sannan ne za su ba su dukiyarsu gaba ɗaya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni cewa masu kula da marayu su jarraba hankulansu, idan sun ga alamar hankali tare da su bayan sun kai shekarun balaga, to su mayar musu da dukiyoyinsu gaba ɗaya. Hakanan kada su riƙa ɗiban dukiyarsu ba tare da wata buƙata ba har su ƙetare iyakar da Allah ya halatta musu. Kada kuma su yi gaggawar ci musu dukiya wai don gudun kada su girma su karɓe dukiyar su hana su komai daga cikinta. Allah kuma ya bayyana cewa, mai kula da dukiyar maraya, idan yana da wadata ba mabuƙacin komai ba ne daga wannan dukiyar, to ya yi kawaici kar ya taɓa wani abu na dukiyar ko da wanda aka halatta masa ne, kamar ladan kasuwanci da yake yi da wannan dukiya. Wanda kuwa yake mabuƙaci ne, to yana iya ɗiban wani abu daga dukiyar kamar ladan wahalar da yake yi a cikinta, gwargwadon abin da ya dace bisa ga yadda al'ada ta gudana.

An karɓo daga A'isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: "Wannan ayar ta sauka ne game da mutumin da yake kula da maraya da dukiyarsa, to idan mabuƙaci ne sai ya ci daga wannan dukiyar gwargwadon yadda ya dace". [Bukhari #2212 da Muslim #3019].

Har wa yau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da idan sun mayar wa marayu dukiyoyinsu gaba ɗaya, to su kafa shaida a kan hakan, don gudun samun wani saɓani nan gaba. Kuma Allah ya isa ya zama mai hisabi ga duk wani mai kula da dukiyar marayu, yana ganin duk abin da yake gudana har zuwa lokacin da zai miƙa dukiyar gaba ɗaya, don haka shi ma shaida ne game da abin da ya wakana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yadda Musulunci yake ƙarfafa zumunci tsakanin ‘yan’uwa, don haka ya yi umarni da a bai wa waɗanda suka halarci rabon gadon ɗan’uwansu da ya rasu wani abu daga cikin wannan dukiyar, don rage musu raɗaɗin da ke cikin zukatansu da kuma ƙara ƙulla zumunta tsakanin dangi ɗaya.

2. Ana so idan ka yi wa wani kyauta, to ka faɗa masa magana mai daɗi da za ta faranta masa rai, kuma kada ka yi tunanin yi masa gori, domin gori yana daga cikin manya-manyan laifuka.
3. Wanda duk ya kyautata wa ‘ya’yan wasu shi ma Allah zai haɗa ‘ya’yansa da masu kyautata musu bayan rasuwarsa.

4. An gabatar da dangi a kan marayu da mabuƙata wajen taimakawa da wani abu daga cikin dukiyar gado yayin da suka halarci rabonta, saboda haƙƙin makusanta yana gaba da haƙƙin waɗanda ba su ba.

5. Irin laifin mutum irin sakamakon da za a yi masa, don haka ya zamana sakamakon mai cin dukiyar marayu ba bisa haƙƙi ba ya kasance yana cin wuta ne a cikinsa, kuma a ƙona shi da ita.

Suratun Nisa’i (7-10)
لِّلرِّجَالِ نَصِيبٌ مِّمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَانِ وَٱلْأَقْرَبُونَ وَلِلنِّسَآءِ نَصِيبٌ مِّمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَانِ وَٱلْأَقْرَبُونَ مِمَّا قَلَّ مِنْهُ أَوْ كَثُرَ ۚ نَصِيبًا مَّفْرُوضًا ﴿٧﴾ وَإِذَا حَضَرَ ٱلْقِسْمَةَ أُوْلُواْ ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينُ فَٱرْزُقُوهُم مِّنْهُ وَقُولُواْ لَهُمْ قَوْلًا مَّعْرُوفًا ﴿٨﴾ وَلْيَخْشَ ٱلَّذِينَ لَوْ تَرَكُواْ مِنْ خَلْفِهِمْ ذُرِّيَّةً ضِعَٰفًا خَافُواْ عَلَيْهِمْ فَلْيَتَّقُواْ ٱللَّهَ وَلْيَقُولُواْ قَوْلًا سَدِيدًا ﴿٩﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَأْكُلُونَ أَمْوَٰلَ ٱلْيَتَٰمَىٰ ظُلْمًا إِنَّمَا يَأْكُلُونَ فِى بُطُونِهِمْ نَارًا ۖ وَسَيَصْلَوْنَ سَعِيرًا ﴿١٠﴾

7. Mazaje suna da wani kaso daga abin da mahaifa da dangi mafiya kusanci suka bari, haka mata su ma suna da wani kaso cikin abin da mahaifa da dangi mafiya kusanci suka bari, daga abin da yake ɗan kaɗan ko mai yawa. Kaso ne wanda an riga an rarraba shi.

8. Kuma idan dangi makusanta da marayu da mabuƙata suka halarci rabon gado, to ku arzurta su daga cikin wannan dukiya, kuma ku faɗa musu magana mai daɗi.

9. Waɗanda suke jin tsoron za su mutu su bar ‘ya’ya raunana a bayansu, suna kuma jin tsoron a zalunce su, to su kiyaye dokokin Allah, kuma su faɗi magana ta daidai.

10. Lalle waɗanda suke cin dukiyar marayu bisa zalunci, wuta ce kawai suke ci a cikkunansu; kuma da sannu za su shiga wuta mai tsananin ƙuna.

A nan kuma wani hukunci ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake bayyana wa wanda ya shafe abin da Larabawa suke yi a jahiliyya, na hana mata gado kwata-kwata. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, maza da mata duka suna gadon dukiyar da iyayensu ko ‘yan’uwansu suka mutu suka bari; kowa yana da kasonsa gwargwadon kusancinsa da mamacin; dukiyar da suka bari kaɗan ce ko mai yawa. Kuma wannan rabon da aka ambata ba na al’ada ne da za su yi shi kamar yadda suka ga dama ba; rabo ne wanda Allah ne da kansa ya yi shi, kuma ya wajabta aiki da shi. Idan wasu daga cikin dangin mamaci waɗanda ba su da gadonsa ko marayu ko miskinai suka halarci wurin rabon, to kada a ƙyale su su tafi ba tare da an yi musu wani ɗan hasafi ba; a ba su ɗan wani abu daga cikin wannan dukiyar ta fuskar ihsani da kyautatawa, domin su ma a daɗaɗa musu, sannan a faɗa musu magana mai daɗi.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake nanata batun kiyaye haƙƙin marayu domin girman lamarinsu, yana mai umartar masu kula da dukiyoyin marayu da cewa, su ji tsoron Allah, su tsaya su kula da wannan amana da take hannayensu, su mu'amalanci waɗannan marayu kamar yadda suke so a mu'amalanci 'ya'yansu raunana da za su mutu su bar su. Idan sun kyautata wa waɗannan, su ma za a kyautata wa 'ya'yansu yayin da suka rasu suka bar su. Don haka su ji tsoron Allah su faɗi maganar da take ta daidai ce.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi alƙawarin narkon azaba ga masu cin dukiyoyin marayu ba bisa haƙƙi ba da cewa, suna cin wuta ne balbal a cikinsu, kuma za a ƙona su da wutar Sa'ira mai tsananin ƙuna.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku nisanci abubuwa masu halakarwa guda bakwai." Sahabbai suka ce: "Waɗanne abubuwa ne?" Sai ya ce: "Shirka da Allah da sihiri da kashe rai wadda Allah ya haramta ba da haƙƙi ba da cin kuɗin riba da cin dukiyar maraya da gudu ranar yaƙi da yi wa mata muminai gafalallu ƙazafi." [Bukhari #6807, da Muslim #89].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1 Allah yana tausayin bawansa fiye da iyayensa da suka haife shi, don haka ne ma shi ne yake yi wa iyaye wasiyya game da haƙƙoƙin 'ya'yansu.

2 Girman sha'anin gado ne ya sa Allah ya buɗe ayoyin rabonsa da kalmar wasiyya, wadda take nufin umarni mai ƙarfi da ya wajaba a kula da shi.

3 Da Allah ya ce a ba wa namiji kaso biyu na 'ya mace, wannan ya nuna cewa idan babu wata mace tare da shi, shi kaɗai ne, to zai karɓe dukiyar gaba ɗayanta. Domin Allah ya sanya wa mace rabin gado yayin da take ita kaɗai ce, to ka ga idan namiji ya zama shi kaɗai ne, to za a ba shi ninkin hakan biyu, shi ne dukan dukiyar.

4 Tabbatar da ƙarancin ilimin ɗan'adam dangane da wanda ya fi kusanci da shi, watau iyayen da suka haife shi ko 'ya'yan da ya haifa. Allah ya nuna ɗan'adam bai san wane ne zai fi amfanar sa a cikinsu ba.

5 Ayoyin nan gaba ɗaya Allah ya gabatar da namiji a kan mace, lokacin da yake magana a kansu, wanda yin hakan shi ya kamata a tsarinsa, yayin da ake magana da maza da mata, a fara ambaton mazan kafin matan, saɓanin yadda Bature yake yi, kuma wasu Musulmi suke kwaikwayon sa a makance ba tare da sanin dalili ba.

Suratun Nisa'i (11-14)
يُوصِيكُمُ ٱللَّهُ فِيٓ أَوۡلَٰدِكُمۡۖ لِلذَّكَرِ مِثۡلُ حَظِّ ٱلۡأُنثَيَيۡنِۚ فَإِن كُنَّ نِسَآءَ فَوۡقَ ٱثۡنَتَيۡنِ فَلَهُنَّ ثُلُثَا مَا تَرَكَۖ وَإِن كَانَتۡ وَٰحِدَةٗ فَلَهَا ٱلنِّصۡفُۚ وَلِأَبَوَيۡهِ لِكُلِّ وَٰحِدٖ مِّنۡهُمَا ٱلسُّدُسُ مِمَّا تَرَكَ إِن كَانَ لَهُۥ وَلَدٞۚ فَإِن لَّمۡ يَكُن لَّهُۥ وَلَدٞ وَوَرِثَهُۥٓ أَبَوَاهُ فَلِأُمِّهِ ٱلثُّلُثُۚ فَإِن كَانَ لَهُۥٓ إِخۡوَةٞ فَلِأُمِّهِ ٱلسُّدُسُۚ مِنۢ بَعۡدِ وَصِيَّةٖ يُوصِي بِهَآ أَوۡ دَيۡنٍۗ ءَابَآؤُكُمۡ وَأَبۡنَآؤُكُمۡ لَا تَدۡرُونَ أَيُّهُمۡ أَقۡرَبُ لَكُمۡ نَفۡعٗاۚ فَرِيضَةٗ مِّنَ ٱللَّهِۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمٗا ١١ ۞وَلَكُمۡ نِصۡفُ مَا تَرَكَ أَزۡوَٰجُكُمۡ إِن لَّمۡ يَكُن لَّهُنَّ وَلَدٞۚ فَإِن كَانَ لَهُنَّ وَلَدٞ فَلَكُمُ ٱلرُّبُعُ مِمَّا تَرَكۡنَۚ مِنۢ بَعۡدِ وَصِيَّةٖ يُوصِينَ بِهَآ أَوۡ دَيۡنٖۚ وَلَهُنَّ ٱلرُّبُعُ مِمَّا تَرَكۡتُمۡ إِن لَّمۡ يَكُن لَّكُمۡ وَلَدٞۚ فَإِن كَانَ لَكُمۡ وَلَدٞ فَلَهُنَّ ٱلثُّمُنُ مِمَّا تَرَكۡتُمۚ مِّنۢ بَعۡدِ وَصِيَّةٖ تُوصُونَ بِهَآ أَوۡ دَيۡنٖۗ وَإِن كَانَ رَجُلٞ يُورَثُ كَلَٰلَةً أَوِ ٱمۡرَأَةٞ وَلَهُۥٓ أَخٌ أَوۡ أُخۡتٞ فَلِكُلِّ وَٰحِدٖ مِّنۡهُمَا ٱلسُّدُسُۚ فَإِن كَانُوٓاْ أَكۡثَرَ مِن ذَٰلِكَ فَهُمۡ شُرَكَآءُ فِي ٱلثُّلُثِۚ مِنۢ بَعۡدِ وَصِيَّةٖ يُوصَىٰ بِهَآ أَوۡ دَيۡنٍ غَيۡرَ مُضَآرّٖۚ وَصِيَّةٗ مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَلِيمٞ ١٢ تِلۡكَ حُدُودُ ٱللَّهِۚ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ يُدۡخِلۡهُ جَنَّٰتٖ

تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١٣ وَمَن يَعۡصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَتَعَدَّ حُدُودَهُۥ يُدۡخِلۡهُ نَارًا خَٰلِدٗا فِيهَا وَلَهُۥ عَذَابٞ مُّهِينٞ ١٤

11. Allah Yana yi muku wasiyya game da ‘ya’yanku; namiji ɗaya yana da rabon ‘ya’ya mata biyu. Amma idan sun kasance mata ne biyu ko fiye da biyu, to suna da kaso biyu bisa uku na abin da ya bari; kuma idan ta kasance ‘ya ce guda ɗaya to tana da rabi. Kuma kowane ɗaya daga cikin mahaifansa biyu yana da kaso ɗaya bisa shida daga cikin abin da ya bari in ya kasance yana da ɗa ko ‘ya. Idan kuma ya kasance ba shi da ɗa ko ‘ya, kuma mahaifansa biyu ne za su ci gadonsa, to mahaifiyarsa tana da kaso ɗaya bisa uku. Amma idan yana da ‘yan’uwa, to mahaifiyarsa tana da kaso ɗaya bisa shida; bayan an fitar da wasiyyar da aka yi ko kuma bashi. Iyayenku da ‘ya’yanku, ba ku san daga cikinsu wane ne zai fi yi muku amfani ba. Rabo ne daga Allah. Lalle Allah Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai cikakkiyar hikima.

12. Kuma kuna da rabin abin da matanku suka bari in ya kasance ba su da ɗa ko ‘ya, amma idan sun kasance suna da ɗa ko ‘ya, to kuna da kaso ɗaya bisa huɗu na abin da suka bari, bayan zartar da wasiyyar da suka yi ko kuma bashi. Kuma suna da kaso ɗaya bisa huɗu na abin da kuka bari, in ya kasance ba ku da ɗa ko ‘ya. Amma idan ya kasance kuna da ɗa ko ‘ya to (matanku) suna da kaso ɗaya cikin takwas na abin da kuka bari, bayan zartar da wasiyyar da kuka yi ko kuma bashi. Amma idan namiji ne za a gaje shi a matsayin *kalala* ko mace, kuma yana da ɗan’uwa guda ɗaya ko ‘yar’uwa guda ɗaya, to kowanne ɗaya yana da kaso ɗaya bisa shida. Amma idan sun fi haka yawa, to za su yi tarayya cikin kaso ɗaya bisa uku, bayan zartar da wasiyyar da aka yi ko kuma bashi, ba wanda zai cutar da (magadansa) ba. Allah Yana yi muku wasiyya matuƙar wasiyya. Allah kuma Mai cikakken sani ne, Mai haƙuri.

13. Waɗannan iyakoki ne na Allah. Wanda duk yake bin Allah da Manzonsa, to zai shigar da shi gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu. Kuma wannan shi ne rabo mai girma.

14. Wanda kuma yake saɓa wa Allah da Manzonsa, yake kuma ƙetare iyakokinsa, to zai shigar da shi wuta, yana mai dawwama a cikinta, kuma yana da wata azaba mai wulaƙantarwa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin rabon gado ne filla-filla bayan ya yi bayaninsa a dunƙule a ayar da ta gabata. Allah ya kira wannan umarni da suna ‘wasiyya’, domin nuna girman sha’aninsa da muhimmancinsa. Larabawa a lokacin Jahiliyya suna hana mata da marasa ƙarfi kamar marayu gadonsu, sai Allah ya hana wannan zalunci, ya yi umarni a ba wa mace gado kamar yadda ake ba wa namiji gado, ko da kuwa ba a daidaita su wajen abin da ake ba su ba, kamar yadda ya hana cin dukiyar marayu.

An karɓo daga Jabiru ɗan Abdullahi (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: Annabi (ﷺ) shi da Abubakar sun zo unguwar Banu Salima don su duba ni, ba ni da lafiya. Sai Annabi (ﷺ) ya same ni ba na cikin hayyacina, sai ya ce a kawo masa ruwan alwala, da aka kawo, ya yi alwala, sai ya zuba mini sauran a kaina sai na farfaɗo, sai na ce: “Me za ka umarce ni da in aikata dangane da dukiyata?” Sai wannan ayar ta sauka: “Allah yana yi muku wasiyya game da ‘ya’yanku….” [Bukhari #4577, da Muslim #1616].

An karɓo daga Jabiru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Matar Sa’ad ɗan Rabi’u (Allah ya ƙara masa yarda) ta zo wurin Annabi (ﷺ) tare da ‘ya’yanta mata biyu da suka haifa da Sa’ad, sai ta ce: “Ya Manzon Allah, waɗannan ‘ya’yan Sa’ad ɗan Rabi’u ne; babansu ya yi shahada a yaƙin Uhudu da ya fita tare da kai, to amma baffansu ya riƙe dukiyarsu, kuma ba wanda zai aure su sai idan suna da dukiya.” Sai Annabi (ﷺ)

ya ce: “Allah zai yanke hukunci a kan haka.” Sai ayar gado ta sauka, sai Manzon Allah (ﷺ) ya aika wa baffansu ya zo, Annabi (ﷺ) ya ce masa: “Ka ba wa ‘ya’yan Sa’ad mata su biyu kaso biyu bisa uku na dukiyar, ita kuma mahaifiyarsu ka ba ta kaso ɗaya cikin takwas, sauran ka riƙe naka ne.” [Abu Dawud #2872, da Tirmizi #2029, da Ibn Maja #2720, da Ahmad #14840].

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda rabon gadon zai kasance, da kason kowa daga cikin magada. Idan mamaci ya mutu ya bar ‘ya’ya maza da mata, to za a ba namiji rabo daidai da na ‘ya’ya mata biyu, idan kuma mamaci ya bar ‘ya’ya mata ne zalla daga biyu abin da ya yi sama, to za a ba su kaso biyu bisa uku na abin da mamaci ya bari. Idan kuwa ‘ya mace ce ɗaya kawai ya bari, to tana da rabin abin da ya bari. Idan kuma ya rasu ne ya bar ‘ya’yansa da iyayensa biyu, to uwa da uba kowannensu za a ba shi kaso ɗaya cikin shida, su kuma ‘ya’yan su raba sauran kamar yadda ayar baya ta yi bayani. Idan kuwa bai bar ‘ya’ya ko jikoki na ɓangaren ‘ya’ya maza ba, to za a ba mahaifiyar kaso ɗaya cikin uku, sauran kuma a ba wa mahaifinsa gaba ɗaya. To amma idan ya bar ‘yan’uwansa shaƙiƙai ko li’abbai ko li’ummai tare da iyayensa biyu, to za a ba wa mahaifiyarsa kaso ɗaya cikin shida, sauran kuma mahaifinsa ya ɗauke, ‘yan’uwansa ba su da komai. To duk wannan rabo za a yi shi ne bayan an zartar da wasiyyar mamaci daga dukiyarsa, amma kada ta wuce kaso ɗaya cikin uku na dukiyar, kuma an biya bashin da ake bin sa. Sannan Allah ya bayyana cewa, ya ba wa kowa haƙƙinsa na gado daga cikin su iyaye da ‘ya’ya, domin ɗan'adam bai san wane ne tsakanin mahaifinsa da ɗansa zai fi zama mai amfani a gare shi ba. Mahaifinsa zai iya zama shi ne mai amfani gare shi fiye da ɗansa, hakanan kuma ɗansa zai iya zama shi ne mafi amfani gare shi fiye da mahaifinsa, don haka bai dace a hana wani haƙƙinsa na gado ba. Wannan rabo daga Allah ne, kuma shi ne masanin komai, don haka ya fi kowa sanin wanda ya dace a ba wa gado da gwargwadon yadda ya dace a ba shi, kuma shi ne gwani mai hikima, wanda yake saka komai a muhallinsa da ya dace da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin gadon ma’aurata. Ya bayyana cewa, idan matar mutum ta rasu kuma ba ta da ɗa namiji ko ‘ya mace, to mijinta yana da gadon rabin dukiyar da ta bari. Idan kuwa tana da ɗa ko ‘ya ɗaya ko da yawa, to mijin yana da kaso ɗaya cikin huɗu na dukiyar da ta bari. Duk kuma wannan rabo za a yi shi ne bayan an cire wasiyyar da ita mai rasuwar ta bari, an kuma biya bashin da ake bin ta. Hakanan ita ma mace idan mijinta ya rasu bai bar ɗa namiji ko ‘ya mace ba, to za a ba ta kaso ɗaya cikin huɗu. Hakanan idan yana da mace fiye da ɗaya, to za su yi tarayya ne a wannan kason. Idan kuma mai rasuwar ya bar ɗa ko ‘ya ɗaya ko da yawa, to matarsa ko matansa suna da kaso ɗaya cikin takwas na abin da ya bari. Kuma duk wannan zai kasance ne bayan an cire wasiyyar da ya bari, an kuma biya bashin da yake kansa. Idan kuma mai rasuwar, mace ko namiji, ba shi da ‘ya’ya, ba shi da iyaye, amma yana da ɗan’uwa ko ‘yar’uwa na ɓangaren mahaifiyarsa; watau wanda suka uwa kawai; to kowanne ɗaya daga cikinsu yana da kaso ɗaya cikin shida na abin da ya bari. Amma idan ‘yan’uwan nasa da aka ambata suna da yawa, to gaba ɗayansu za a ba su kaso ɗaya ne cikin uku, su raba daidai, babu fifiko tsakanin mace da namiji. Duk kuwa wannan za a yi shi ne bayan an cire wasiyya da kuma bashi, kuma ba tare da an tauye wa wani magaji haƙƙinsa ko an ƙara wa wani fiye da abin da ya cancanta a ba shi ba. Wannan rabon gadon duk wasiyya ce daga Allah da ta wajaba muminai su rungume ta, su yi aiki da ita. Allah masani ne, ya san komai na masalahar bayinsa, ya kuma san abin da zai cutar da su, ya san wane ne ya cancanta a ba shi gado, ya san wanda bai cancanta a ba shi ba, kuma mai haƙuri ne, ba ya gaggawar yin uƙuba ga wanda ya saɓa masa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafa cewa, abin da ya shar’anta na rabon gado da kason da za a ba wa kowa, iyakokinsa ne, ya wajaba a kan bayi lalle kada su ƙetare su. Sannan ya bayyana sakamakon wanda ya yi biyayya gare shi da kuma Manzonsa, da cewa yana da gidajen Aljanna, waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarkashinsu, kuma za su dawwama a cikinsu har abada. Wannan kuma shi ne babban rabo. Amma wanda ya saɓa wa Allah da Manzonsa, kuma ya ƙetare iyakokin Allah, to Allah zai shigar da shi wutar Jahannama, zai yi ta zama a cikinta har abada, kuma yana da wata azaba ta wulaƙanci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1 Zaman mata a gidajensu yana daga cikin hanyoyin hana yaɗuwar ɓarna a cikin al'umma.

2 Ya kamata mu bayi mu dinga tausaya wa masu laifuka waɗanda suka tuba, suka gyara ayyukansu; kada mu ci gaba da tsangwamar su a kan laifukan da suka gabata. Wannan shi zai taimaka wa waɗanda suka tuba su ɗore a kan tubansu.
3 Asalin abin da yake jefa mutane cikin aikata laifi shi ne jahiltar illar da take tattare da laifin, ko kuma zaton laifin da za su aikata ɗin yana da wani amfani da ya fi cutarwarsa. Wanda duk ya yi wani aiki na saɓo, to jahili ne, ko da kuwa ya san ba a kan gaskiya yake ba.

4 Wajabcin gaggauta tuba zuwa ga Allah domin mutum bai san lokacin mutuwarsa ba.

5 An sharɗanta samun shaidu maza kafin tsayar da haddin zina, domin shaidarsu ta fi ta mata saboda sun fi mata kiyaye abubuwa, shi kuma haddi ana sarayar da shi yayin da aka sami wata shubuha ta shigo.

6 Babu mai wajabta wa Allah wani abu sai abin da shi ya wajabta wa kansa, domin shi ne yake yin abin da ya ga dama.

Suratun Nisa'i (15-18)
وَٱلَّٰتِي يَأۡتِينَ ٱلۡفَٰحِشَةَ مِن نِّسَآئِكُمۡ فَٱسۡتَشۡهِدُواْ عَلَيۡهِنَّ أَرۡبَعَةٗ مِّنكُمۡۖ فَإِن شَهِدُواْ فَأَمۡسِكُوهُنَّ فِي ٱلۡبُيُوتِ حَتَّىٰ يَتَوَفَّىٰهُنَّ ٱلۡمَوۡتُ أَوۡ يَجۡعَلَ ٱللَّهُ لَهُنَّ سَبِيلٗا ١٥ وَٱلَّذَانِ يَأۡتِيَٰنِهَا مِنكُمۡ فَـَٔاذُوهُمَاۖ فَإِن تَابَا وَأَصۡلَحَا فَأَعۡرِضُواْ عَنۡهُمَآۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ تَوَّابٗا رَّحِيمًا ١٦ إِنَّمَا ٱلتَّوۡبَةُ عَلَى ٱللَّهِ لِلَّذِينَ يَعۡمَلُونَ ٱلسُّوٓءَ بِجَهَٰلَةٖ ثُمَّ يَتُوبُونَ مِن قَرِيبٖ فَأُوْلَٰٓئِكَ يَتُوبُ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ١٧ وَلَيۡسَتِ ٱلتَّوۡبَةُ لِلَّذِينَ يَعۡمَلُونَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ حَتَّىٰٓ إِذَا حَضَرَ أَحَدَهُمُ ٱلۡمَوۡتُ قَالَ إِنِّي تُبۡتُ ٱلۡـَٰٔنَ وَلَا ٱلَّذِينَ يَمُوتُونَ وَهُمۡ كُفَّارٌۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَعۡتَدۡنَا لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمٗا ١٨

15. Kuma waɗannan da suke aikata zina daga cikin matanku, to ku kafa musu shaidu guda huɗu daga cikinku, sannan idan sun bayar da shaida, to sai ku tsare su a cikin gidaje har sai mutuwa ta ɗauke su ko kuma Allah Ya sanya musu wata mafita.

16. Kuma maza biyu daga cikinku da za su yi zina, to ku muzguna musu; amma idan sun tuba kuma suka gyara ayyukansu, to ku kawar da kai daga gare su. Lalle Allah Ya kasance Mai yawan karɓar tuba ne, Mai jin ƙai.

17. Tuban da Allah Yake karɓa kawai (ita ce) na waɗanda suke aikata mummunan aiki da jahilci, sannan su gaggauta tuba, to waɗannan Allah zai karɓi tubansu. Allah kuma Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima.

18. Kuma ba a karɓar tuba daga waɗanda suke aikata munanan ayyuka har sai lokacin da mutuwa ta zo wa ɗayansu, sai ya ce: "Ni kam na tuba yanzu;" kuma ba a karɓar tuban waɗanda suke mutuwa alhalin suna kafirai. Waɗannan Mun yi musu tanadin azaba mai raɗaɗi.

Kafin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da hukuncin bulala ga mazinatan da ba su taɓa yin aure ba, ko jefewa ga waɗanda suka taɓa yin aure, Allah ya yi umarni ne da a tsare matan da aka same su da laifin zina a gidaje, kada a bar su su fita har mutuwa ta zo musu, ko kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya samar musu da wata mafita. Kuma hukuncin bai bambance matan aure da waɗanda ba su yi aure ba.

Za a yanke musu wannan hukunci ne bayan an samu shaidu maza Musulmi huɗu adalai sun bayar da shaida da cewa sun gan su suna zina.
Hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su gallaza wa waɗanda suka yi zina daga cikinsu, maza ko mata, ta hanyar yi musu kakkausar magana da tsawatarwa da sauransu. Idan kuma sun tuba sun bar wannan babban laifi, sun gyara rayuwarsu, to sai muminai su ƙyale su, domin Allah mai karɓar tuban wanda ya tuba ne, kuma mai tausayi ne ga bayinsa, kuma ƙofar tuba koyaushe a buɗe take. Daga baya ne Allah ya saukar da hukuncin da ya shafe wannan, kamar yadda ya bayyana a cikin *Suratun Nur*, aya ta 2, da kuma hadisan Manzon Allah (ﷺ).

An karɓo daga Ubadatu ɗan Samit (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Ku karɓa daga gare ni! Ku karɓa daga gare ni! Haƙiƙa Allah ya samar musu da mafita "Budurwa da saurayi a yi musu bulala ɗari a kuma tsare su shekara guda; bazawara da bazawari a yi musu bulala ɗari sannan a jefe su." [Muslim #1690].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yana karɓar tuban wanda duk ya yi laifi cikin jahilci. Domin duk wanda ya saɓa wa Allah, to shi jahili ne ko da kuwa yana da ilimin haramcin laifin da ya yi, domin aikata laifin da ya yi shi ne jahilcin da wautar, kamar yadda Ƙatada ya ce: "Sahabban Manzon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sun haɗu a kan cewa, duk abin da aka saɓa wa Allah da shi jahilci ne." [Tafsirin Abdurrazak 1:137].
Allah ya bayyana cewa, yana karɓar tubansu idan sun tuba kafin zuwan mutuwarsu. An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah yana karɓar tuban bawa matuƙar bai zo gargara ba." [Tirmizi #3537, da Ibnu Maja #4253, da Ahmad #6160]. To waɗannan su ne Allah yake yafe musu, ya karɓi tubansu. Allah kuwa ya kasance mai cikakken ilimi ne a kan komai, kuma mai hikima.
To amma waɗanda suke aikata saɓo, sannan ba su tashi tuba ba sai da suka yi ido huɗu da mutuwa sai a sannan su ce sun tuba, to waɗannan Allah ba ya karɓar tubansu, kamar yadda ba ya karɓar tuban wanda ya mutu yana kafiri. Waɗannan kuma Allah ya yi musu tanadin azaba mai raɗadi da take jiran su a lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Musulunci yana kwaɗaitar da Musulmi su riƙa haƙuri da matansu ko da za su ga wani abu tare da su wanda ba sa so, domin tana yiwuwa ya kasance Allah ya sanya alheri mai yawa a cikin zama da su wanda mutum bai san da shi ba.

2. Mutum bai san gaibu ba. Sonsa ko ƙinsa ga wani abu ba shi ne ma'auni na amfanin abin gare shi ko rashin amfaninsa ba; ma'auni shi ne abin da Allah ya zaɓa masa. Kuma abin da ya fi komai amfani ga mutum shi ne biyayyarsa ga mahaliccinsa ta hanyar aiki da umarninsa da barin haninsa. To wannan shi ya fi komai zama alheri ga bawa.

3. Umarni da kyautata mu'amala ga mata. Duk wata mummunar mu'amala wadda za ta sosa rai, wajibi ne miji ya guje ta tsakaninsa da matarsa. Kyautata musu iya ƙoƙarinsa, shi ne harsashin gina gida mai cike da soyayya da girmama juna da fahimtar juna.

4. Yin zina da mace muharrama babban laifi ne da ya kai matuƙa wajen muni, domin ya fi yin zina da wadda ba muharrama ba. Shi ya sa malamai da dama suka ce, duk wanda aka samu ya yi zina da muharramarsa, to za a jefe shi, ko ya taɓa aure ko bai taɓa ba. Shi ya sa Allah ya siffanta wannan aiki da cewa, alfasha ne, abin ƙi ne, kuma mummunar hanya ce. [Dubi *Suratul Isra'i*, aya ta 32].

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا يَحِلُّ لَكُمۡ أَن تَرِثُواْ ٱلنِّسَآءَ كَرۡهٗاۖ وَلَا تَعۡضُلُوهُنَّ لِتَذۡهَبُواْ بِبَعۡضِ مَآ ءَاتَيۡتُمُوهُنَّ إِلَّآ أَن يَأۡتِينَ بِفَٰحِشَةٖ مُّبَيِّنَةٖۚ وَعَاشِرُوهُنَّ بِٱلۡمَعۡرُوفِۚ فَإِن كَرِهۡتُمُوهُنَّ فَعَسَىٰٓ أَن تَكۡرَهُواْ شَيۡـٔٗا وَيَجۡعَلَ ٱللَّهُ فِيهِ خَيۡرٗا كَثِيرٗا ١٩ وَإِنۡ أَرَدتُّمُ ٱسۡتِبۡدَالَ زَوۡجٖ مَّكَانَ زَوۡجٖ وَءَاتَيۡتُمۡ إِحۡدَىٰهُنَّ قِنطَارٗا فَلَا تَأۡخُذُواْ مِنۡهُ شَيۡـًٔاۚ أَتَأۡخُذُونَهُۥ بُهۡتَٰنٗا وَإِثۡمٗا مُّبِينٗا ٢٠ وَكَيۡفَ تَأۡخُذُونَهُۥ وَقَدۡ أَفۡضَىٰ بَعۡضُكُمۡ إِلَىٰ بَعۡضٖ وَأَخَذۡنَ مِنكُم مِّيثَٰقًا غَلِيظٗا ٢١ وَلَا تَنكِحُواْ مَا نَكَحَ ءَابَآؤُكُم مِّنَ ٱلنِّسَآءِ إِلَّا مَا قَدۡ سَلَفَۚ إِنَّهُۥ كَانَ فَٰحِشَةٗ وَمَقۡتٗا وَسَآءَ سَبِيلًا ٢٢

19. Ya ku waɗanda suka yi imani, bai halatta gare ku ku gaji mata a bisa ga tilas ba; kuma kada ku hana su aure don ku ƙwace wani sashi na abin da kuka ba su, sai fa in sun zo da wata alfasha ta sarari. Kuma ku yi musu kyakkyawar mu’amala. Amma idan har kun ƙi su, to mai yiwuwa ne ku ƙi wani abu, Allah kuma Ya sanya alheri mai yawa a cikinsa.

20. Kuma idan kun yi nufin musanya wata mace a gurbin wata macen, kuma kun riga kun ba wa ɗayarsu dukiya mai yawa (ta sadaki), to kar ku karɓi komai daga cikinsa. Shin za ku karɓe shi ne a kan zalunci da laifi ƙarara?

21. Kuma ta yaya za ku karɓe shi alhali kuma kun riga kun sadu da juna, kuma sun riƙi wani alƙawari mai ƙarfi daga wajenku?

22. Kuma kada ku auri wadda iyayenku maza suka aure ta cikin mata, sai fa abin da ya riga ya shuɗe. Lalle yin hakan ya kasance alfasha ce kuma abu ne da zai jawo fushin Allah, kuma tafarki ne wanda ya yi muni.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rushe wasu miyagun al’adu ne na Larabawan zamanin jahiliyya, waɗanda suka ƙunshi zalunci ga mata. Larabawa kafin zuwan Musulunci, idan mutum ya mutu, to magadansa ne za su gaji matarsa da ya bari; idan magajin ya ga dama ya aure ta, ko kuma ya aurar da ita ga wanda yake so ko da kuwa ita ba ta so. Idan kuma ya ga dama ya ƙi auren ta, ya kuma ƙi aurar da ita, ya ƙyale ta nan haka ba aure. Sai Allah ya saukar da wannan ayar yana hana su gadon mata da ƙarfi, ko su hana su yin aure.

An karɓo daga Abu Umamata ɗan Sahlu ɗan Hunaif ya ce: Lokacin da Abu Kais ɗan Al-Aslatu ya rasu, ɗansa ya so ya auri matarsa, domin haka suke yi a jahiliyya, sai Allah ya saukar da faɗarsa: “Ba ya halatta a gare ku ku gaji mata bisa tilas.” [Nasa’i, *As-Sunanul Kubra* 11095, da Tafsirin *At-Tabari* 8:105].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, haramun ne ga muminai su gaji matan ubanninsu ko danginsu da suka mutu, don su aure su ko su aurar da su ga waɗanda su suka so, ko da matan ba sa son su. Hakanan ya hana su su takura wa matansu na aure har su gaji su fanshi kawunansu ta hanyar sadaukar da sadakinsu gaba ɗaya, ko wani abu daga cikinsa, ko su haƙura da wani haƙƙi nasu domin su ƙwaci kawunansu ta hanyar saki. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yin haka bai halatta ba, sai dai idan su matan ne suka aikata wani laifi kamar na zina, ko suka bijire wa mijin ba tare da wani dalili ba, to a wannan lokacin ya halatta miji ya nemi a mayar masa da sadakinsa ko wani abu daga cikinsa domin ya sake ta.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mazaje da su yi kyakkyawar mu’amala ga matansu, ta hanyar nuna musu halaye na ƙwarai da magana mai daɗi da guje wa duk wani abin da zai sosa musu rai, kuma su kula da haƙƙoƙinsu na ciyarwa da tufatarwa da sauran abin da shari’a ta umarce su da shi da kuma abin da ya gudana a al’ada, kuma bai saba ma wata doka ta Musulunci ba.

An karɓo daga Aisha (Allah ya ƙara masa yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Mafifici daga cikinku shi ne mafifici ga iyalansa, kuma ni ne mafificinku ga iyalaina.” [Tirmizi #3895, da Darimi #2260].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, idan wani abu ya faru har mazaje suka ƙyamaci matansu, to kamata ya yi su yi haƙuri da su, domin tana iya yiwuwa ya zamana akwai wani alheri mai yawa tare da su, kamar su haifa musu ‘ya’ya waɗanda za su amfane su a rayuwarsu ta duniya da ta lahira, ko kuma daga baya su ji suna ƙaunar su.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kada wani mumini ya ƙi wata mumina; idan ya ƙi wata ɗabi’a ce tata, to ai kuma zai so wata ɗabi’ar tata.” [Muslim #1469].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cewa, idan mutum ya ga ba zai iya zama da matarsa ba, ya yi niyyar ya sake ta ya auro wata, alhalin ya ba ta sadaki mai yawa, to bai halatta ya ce zai ƙwace sadakin da ya ba ta ba, ko wani abu daga cikinsa, domin haƙƙinta ne. Allah ya ce, ta yaya za su ƙwace sadakin da suka ba su don za su rabu da su bisa zalunci alhali sun yi alaƙar auratayya a tsakaninsu, kuma sun ɗauki alƙawari mai ƙarfi na za su riƙe su da amana, su ba su duk haƙƙoƙinsu, ba za su cuce su ba?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya taɓo wata al’ada ta jahiliyya, wadda ɗa yake auren matar babansa. Allah ya yi wa muminai kashedi da kada su kuskura su yi wannan kwaɓa, sai dai abin da ya riga ya faru tun kafin zuwan Musulunci, ko kafin a haramta wannan al’adar, to wannan an yafe musu shi. Auren matan iyaye maza wata aika-aika ce mai matuƙar muni, kuma Allah yana ƙyamar wannan aiki, mutane masu hankali ma suna ƙyamar sa. Hasali ma gaba tana iya aukuwa tsakanin ɗan da mahaifinsa saboda kishi.

Suratun Nisa’i (23-24)
حُرِّمَتۡ عَلَيۡكُمۡ أُمَّهَٰتُكُمۡ وَبَنَاتُكُمۡ وَأَخَوَٰتُكُمۡ وَعَمَّٰتُكُمۡ وَخَٰلَٰتُكُمۡ وَبَنَاتُ ٱلۡأَخِ وَبَنَاتُ ٱلۡأُخۡتِ وَأُمَّهَٰتُكُمُ ٱلَّٰتِيٓ أَرۡضَعۡنَكُمۡ وَأَخَوَٰتُكُم مِّنَ ٱلرَّضَٰعَةِ وَأُمَّهَٰتُ نِسَآئِكُمۡ وَرَبَٰٓئِبُكُمُ ٱلَّٰتِي فِي حُجُورِكُم مِّن نِّسَآئِكُمُ ٱلَّٰتِي دَخَلۡتُم بِهِنَّ فَإِن لَّمۡ تَكُونُواْ دَخَلۡتُم بِهِنَّ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡكُمۡ وَحَلَٰٓئِلُ أَبۡنَآئِكُمُ ٱلَّذِينَ مِنۡ أَصۡلَٰبِكُمۡ وَأَن تَجۡمَعُواْ بَيۡنَ ٱلۡأُخۡتَيۡنِ إِلَّا مَا قَدۡ سَلَفَۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٢٣ *وَٱلۡمُحۡصَنَٰتُ مِنَ ٱلنِّسَآءِ إِلَّا مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُمۡۖ كِتَٰبَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡۚ وَأُحِلَّ لَكُم مَّا وَرَآءَ ذَٰلِكُمۡ أَن تَبۡتَغُواْ بِأَمۡوَٰلِكُم مُّحۡصِنِينَ غَيۡرَ مُسَٰفِحِينَۚ فَمَا ٱسۡتَمۡتَعۡتُم بِهِۦ مِنۡهُنَّ فَـَٔاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ فَرِيضَةٗۚ وَلَا جُنَاحَ عَلَيۡكُمۡ فِيمَا تَرَٰضَيۡتُم بِهِۦ مِنۢ بَعۡدِ ٱلۡفَرِيضَةِۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمٗا ٢٤

23. An haramta muku auren iyayenku mata da ‘ya’yanku mata da ‘yan’uwanku mata da gwaggonninku da ‘yan’uwan mahaifanku mata da ‘ya’yan ɗan’uwanku da ‘ya’yan ‘yar’uwarku da iyayenku waɗanda suka shayar da ku da ‘yan’uwanku mata ta wajen shayarwa, da iyayen matanku da agololinku waɗanda suke cikin gidajenku, waɗanda matan da kuka taɓa saduwa da su suka haife su, in kuwa ba ku taɓa saduwa da su ba, to babu laifi a kanku, da matan ‘ya’yanku maza waɗanda suke na tsatsonku; haramun ne kuma ku haɗa ‘yan’uwa mata biyu, sai dai abin da ya wuce a baya. Lalle Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai jin ƙai.

24. Haka ma da matan aure, sai dai ƙwaraƙwaranku; wannan hukuncin Allah ke nan a kanku. Kuma an halatta muku (sauran) matan da ba waɗannan ba, ku neme su da kuɗinku, kuna masu kame kanku, ba

ma su zina ba. To waɗanda kuka sadu da su daga cikinsu ku ba su sadakinsu wanda kuka yanka musu. Kuma babu laifi a kanku game da abin da kuka yi yarjejeniya da shi bayan sadakin da kuka yanka. Lalle Allah Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima.

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana irin matan da aka haramta wa mutum ya aura saboda dangantaka ta tsatso ko ta shayarwa ko kuma ta surukutaka da waɗanda aka haramta haɗa su a tare da kuma matan da aka halatta auren su.
Waɗanda aka haramta auren su saboda dangantaka ta tsatso su bakwai ne. Su ne:
• Mahaifiya; kaka ta shiga ƙarƙashin wannan, komai nisanta.
• 'Ya; a ƙarƙashinta, duk matan da suka biyo ta tsatsonta sun shiga ciki, kamar jika mace da 'yar jika da abin da ya yi ƙasa.
• 'Yar'uwa, wadda suka haɗa uwa ɗaya uba ɗaya, ko ta wajen uba, ko ta wajen uwa.• Gwaggo, wato 'yar'uwar uba; yayarsa ko ƙanwarsa.
• Inna, wato 'yar'uwar mahaifiya; yayarta ko ƙanwarta.• 'Yar ɗan'uwa, shaƙiƙi ko na wajen uba ko na wajen uwa.
• 'Yar 'yan'uwa, shaƙiƙiya ko ta wajen uba ko ta wajen uwa.Sai kuma waɗanda aka haramta auren su saboda dangantaka ta shayarwa, su kuma su biyu ne:
• Matar da ta shayar da kai nono ta zama mahaifiya ta fuskar shayarwa, mahaifiyarta ta zama kakarka.
• Matar da kuka sha nono ɗaya ta zama 'yar'uwarka, don haka ko 'ya'yanta mata ba za ka aura ba, don 'ya'yanka ne.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa dangane da 'yar baffansa Hamza: "Ba ta halatta gare ni ba, abin da yake haramta saboda dangantaka ta jini, yana haramta saboda dangantaka ta shayarwa, ita 'yar ɗan'uwana ce da muka sha nono ɗaya da shi." [Bukhari #2645, da Muslim #1447].

Sannan sai waɗanda aka haramta saboda surukuta su ne:
• Iyayen matanku na aure. Da zarar an ɗaura masa aure da 'yarta, to ta haramta a gare shi, ya tare da ita ko bai tare ba.
• Agola. Wato 'yar matar da ya aura, kuma ya tare da ita, to 'yar ta haramta a gare shi. Amma idan an ɗaura aure ne kawai ba su tare ba, ya saki uwarta, to zai iya auren 'yar.
• Matar ɗansa na cikinsa. Da zarar an ɗaura wa ɗansa aure da mata, to ta haramta a gare shi, ko da kuwa ɗan bai tare da ita ba ya sake ta.
Sai kuma waɗanda aka hana auren su a tare lokaci guda, su ne 'yan'uwan juna, wato ya da ƙanwa, ko tagwagaye. Idan mutum ya auri yaya ko ya auri ƙanwa, to ba zai auro yayarta ba, har sai in ya sake ta, to yana iya auren ɗayar.
Duk matan da aka ambata kuma aka haramta auren su, Larabawa ma a jahiliyya suna haramta su in ban da biyu kawai, su ne matar uba da kuma haɗa ya da ƙanwa lokaci guda, kamar yadda Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya faɗa. [Dubi, Tafsirin *Tabari* 8:132]. Allah ya ce sai dai abin da ya riga ya wakana tun lokacin jahiliyya ko kafin a haramta hakan, to wannan Allah ya yi afuwa a kansa, domin Allah mai yawan gafara ne, kuma mai jin ƙai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci matan aure cewa su ma haramun ne wani ya aure su yayin da igiyar auren wani tana a wuyansu. Amma Allah ya togace ƙwaraƙwarai ko da kuwa suna da mazaje kafirai kafin a ci su da yaƙi, to su ya halatta a aure su bayan sun yi istibra'i, wato jini ɗaya.
Sunnar Annabi (ﷺ) kuma, har wa yau ta zo da haramta wa mutum ya haɗa auren mace da gwaggonta ko innarta lokaci guda. An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Ba a haɗa tsakanin mace ga gwaggonta, ko tsakanin mace da innarta." [Bukhari #5109 da Muslim #1408].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana cewa, duk abubuwan da ya yi bayani a baya wani farali ne da ya wajabta wa muminai, dole ne su riƙe shi gam-gam. A ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nusantar da cewa, baya ga matan da aka haramta aurensu, sauran matan da ba a ambata ba an halatta wa muminai da su biya sadakinsu, su aure su don su tsare mutuncinsu, ko kuma su sayi ƙwaraƙwarai da kuɗinsu don su tsare kawunansu daga faɗawa laifin zina. Duk matar da aka aura kuma aka sadu da ita, to Allah ya wajabta a biya ta sadakinta. Bayan an yanke sadaki kuma, to babu laifi ga ma'aurata idan suka yi wata yarjejeniya a kansa a tsakaninsu ta ƙari a kan asalin sadakin ko ragi ko yafe masa ko jinkirta biyansa. Lalle Allah masanin komai ne, kuma mai hikima ne a cikin duk hukunce-hukuncensa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin auren mutu'a, domin faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): "Kuna masu kame kanku, ba masu zina ba." Mai auren mutu'a ba ya yin sa don kame kai, domin ba aure ne na shari'a ba, shi ya sa ba shi da wasu hukunce-hukuncen aure har a wurin waɗanda suka halatta shi.

2. Sadaki haƙƙi ne na matar da aka aura, dole ne a ba ta shi, sai dai idan ta yafe daga baya.

3. Kwaɗaitarwa a kan auren mata muminai 'ya'ya, saboda babu inda Allah Ya hana yin haka sai fa idan akwai wata larura ko uzuri.

4. Ba ya halatta ga wanda ya rasa abin da zai auri mace 'ya mumina, ya auri baiwa Ma'abociyar Littafi. Ke nan wanda yake da halin auren 'ya mumina, shi ya fi cancanta a hana shi auren baiwa Ma'abociyar Littafi.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarnin da a auri mata bayi muminai. Saboda Larabawa a jahiliyya ba sa yarda su auri mata bayi sai dai su yi farka da su, sai Allah ya nufi karrama su, ya yi umarni da auren su, domin darajar imaninsu, kuma domin a nuna imani shi ne abin da yake ƙara kusanta muminai ga junansu, har ya kawar da duk wasu bambance-bambance a tsakaninsu.

6. Haramun ne mace ta yi abota da namiji, ko da kuwa ba sa aikata zina a tsakaninsu, domin yin haka buɗe ƙofar fitina ce, wadda za ta iya kaiwa ga lalacewarsu. Shi ya sa aka hana namiji ya kaɗaita da matar da ba muharramarsa ba, ba kuma matarsa ba.

7. Ana guje wa auren baiwa saboda abubuwa kamar haka:
• 'Ya'yan da za ta haifa za su zama bayi.
• Mai yiwuwa ne ta saba fita yawace-yawace da cakuɗuwa da maza.
• Mai gidanta zai iya sayar da ita ga wani mutum daban duk sanda ya ga dama.

Suratun Nisa'i (25)

وَمَن لَّمۡ يَسۡتَطِعۡ مِنكُمۡ طَوۡلًا أَن يَنكِحَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ فَمِن مَّا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُم مِّن فَتَيَٰتِكُمُ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۚ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِإِيمَٰنِكُمۚ بَعۡضُكُم مِّنۢ بَعۡضٖۚ فَٱنكِحُوهُنَّ بِإِذۡنِ أَهۡلِهِنَّ وَءَاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ بِٱلۡمَعۡرُوفِ مُحۡصَنَٰتٍ غَيۡرَ مُسَٰفِحَٰتٖ وَلَا مُتَّخِذَٰتِ أَخۡدَانٖۚ فَإِذَآ أُحۡصِنَّ فَإِنۡ أَتَيۡنَ بِفَٰحِشَةٖ فَعَلَيۡهِنَّ نِصۡفُ مَا عَلَى ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ مِنَ ٱلۡعَذَابِۚ ذَٰلِكَ لِمَنۡ خَشِيَ ٱلۡعَنَتَ مِنكُمۡۚ وَأَن تَصۡبِرُواْ خَيۡرٞ لَّكُمۡۗ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٥

25. Kuma daga cikinku wanda ba shi da yalwar dukiya da zai iya auren ‘ya’ya muminai, to ya aura daga cikin abin da kuka mallaka na kuyanginku muminai. Kuma Allah Shi ne Mafi sanin imaninku. Sashinku ‘yan’uwan sashi ne. To ku aure su da izinin iyayen gidansu. Sai ku ba su sadakinsu ta hanyar da ta dace, suna masu kame kawunansu ba mazinata ba, sannan ba waɗanda suke riƙar farka a ɓoye ba. To idan sun yi aure, sannan suka yi zina, to abin da za a yi musu na azaba, shi ne rabin abin da ake yi wa ‘ya’ya. Wannan ya shafi wanda ya ji tsoron matsatsi a cikinku. Amma ku yi haƙuri shi ya fi muku alheri. Allah kuma Mai yawan gafara ne, Mai jin ƙai.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin matan da ba su halatta mutum ya aura ba da waɗanda suka halatta ya aura, sai kuma ya kawo bayanin auren mata waɗanda suke bayi. Duk da cewa auren baiwa halal ne, sai dai shari’a ba ta ƙarfafa yin sa ba sai bisa larura, saboda matsalar da take tattare da shi, domin ɗan da mutum zai haifa zai zama bawa ne. Don haka sai Allah ya nuna cewa sai idan mutum ba shi da halin auren mace ‘yantacciya saboda rashin kuɗin sadaki ko wani dalili, to sannan ne zai auri baiwa mumina mallakar ‘yan’uwansa muminai, idan sun zamanto muminai ne kamar yadda ya bayyana gare ku a zahiri, Allah shi ne mafi sanin gaskiyar imaninku da nasu. Ku da sauran bayi duk daidai kuke wajen mutuntaka, domin dukkanku asalinku shi ne Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Hakanan mata ‘yantattu da mata bayi ta wannan fuskar ɗaya suke, don haka idan har akwai larura ta kasa auren mace ‘ya, to kada ku ƙyamaci auren baiwar mumina. Kuma a aure su bisa amincewar iyayen gijinsu, a ba su sadakinsu kamar yadda shari’a ta ajiye, kada a tauye musu komai, ko a yi ta wasa da hankulansu. A aure su bisa sharadin su zamanto masu kame kansu, kuma ba masu yin zina ba a bayyane ko a ɓoye. To idan suka yi aure, sannan kuma suka aikata zina, to sai a yi musu haddi rabin wanda ake yi wa mace ‘ya wadda ba ta yi aure ba, wato a yi musu bulala hamsin.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, ya halatta auren mata bayi ne kawai ga wanda ba zai iya daurewa ya zauna ba aure ba, saboda yana tsoron faɗawa cikin zinace-zinace. Da a ce mazan za su daure su yi haƙuri har Allah ya hore musu abin auren mace ‘yantacciya to da ya fi musu alheri. Lalle Allah mai gafara ne ya ɗauke laifi ga wanda ya cika sharuɗɗan da aka ambata, kuma mai rahama ne, ba ya takura wa bayinsa a cikin duk abin da yake shar’anta musu.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yalwar rahamar Allah ga bayinsa, ta hanyar yi musu bayanin addininsu filla-filla, bai bar su cikin jahilci ba.

2. Babu wani hukunci na shari’a wanda ba a yi bayaninsa ba, sai dai wasu su jahilci wasu abubuwa, ko dai saboda ƙarancin ilimi ko kuma rashin fahinta ko kuma wani mummunan nufi.

3. Kamalar wannan al’umma da shari’arta. Duk wani alheri da wata al’umma da ta gabata ta samu, to wannan al’ummar tana da nata babban rabon a cikinsa.

4. Yin hattara da taka-tsantsan game da bin sha’awace-sha’awacen ‘yan duniya, waɗanda koyaushe abin da suke son gani shi ne su ga mun kauce wa hanyar shiriya, mun kama hanyar sharholiya, daga nan sai rayuwarmu ta lalace, mu yi ta samun koma-baya tare da faɗawa cikin fushin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Hattara da ‘yan bidi’a, waɗanda suka kasu gida biyu, ‘yan shubuha, da kuma ‘yan sha’awa, wato ‘yan tamore. Jahilin cikinsu yana cike da ruɗani, ya kasa tantancewa tsakanin ƙarya da gaskiya; mai ilimin cikinsu kuwa ƙoƙarinsa yadda zai biya buƙatar sha’awarsa ne kawai, ba Allah ne da Manzonsa a zuciyarsa ba.

6. Kaskancin mutanen da suke bin sha’awace-sha’awacensu ya dabaibaye su har suka zama su ne suke yi musu jagora.

7. ‘Yan duniya ‘yan ta-more bukatarsu kullum ita ce, su ga mun kauce wa hanya gaba ɗaya. Duk sanda suka ga mun ɗan fara karkacewa, to za su daɗa mana ƙaimi don su ga mun karkace sosai.

8. Maimaita ambaton tuba a wannan wuri har sau biyu, yana nuna yadda bin sha’awa yake da ƙarfi a zukata, don haka akwai bukatar a yi ta nanata batun tuba don nuna girman bukatarta a koyaushe.

9. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fi son sauki ga kowane lamari fiye da a tsananta, musamman game da abin da shari’a ta bayar a wasu wurare.

10. Duk lokacin da wasu hujjoji biyu suka yi karo da juna, kuma mai nazari ya kasa rinjayar da guda ɗaya daga cikinsu, to yana da kyau ya zabi ɓangaren da ya fi sauki a kan wanda yake da tsanani.

11. Faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): “Allah yana nufin yi muku bayani, kuma ya shiryar da ku.” da faɗarsa: “Kuma Allah yana nufin ya karɓi tubanku.” da faɗarsa: “Allah yana nufin ya sassauta muku.” duk waɗannan ayoyi suna da dangantaka da juna, saboda bawa yana da halaye guda uku: Halin jahiltar halal da haram, sai aka yi batun yi masa bayani da shiriyar da shi; halin gazawa, sai aka ambata masa tuba; sai kuma halin rauni da ƙarancin juriya, sai aka ambaci sassautawa.

12. Duk yadda mutum ya kai da ji-ji da kansa, to ya riƙa tuna asalinsa da cewa an halicce shi mai rauni, don haka wace ɗagawa kuma zai yi?

Suratun Nisa’i (26-28)

يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُبَيِّنَ لَكُمۡ وَيَهۡدِيَكُمۡ سُنَنَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ وَيَتُوبَ عَلَيۡكُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٢٦ وَٱللَّهُ يُرِيدُ أَن يَتُوبَ عَلَيۡكُمۡ وَيُرِيدُ ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ ٱلشَّهَوَٰتِ أَن تَمِيلُواْ مَيۡلًا عَظِيمٗا ٢٧ يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُخَفِّفَ عَنكُمۡۚ وَخُلِقَ ٱلۡإِنسَٰنُ ضَعِيفٗا ٢٨

26. Allah Yana nufin yi muku bayani ne, kuma Ya shiryar da ku hanyoyin waɗanda suka gabace ku, kuma Ya karɓi tubanku. Kuma Allah Mai yawan sani ne, Mai hikima.

27. Kuma Allah Yana nufin Ya karɓi tubanku ne, amma waɗanda suke bin sha’awace-sha’awace, su kuma suna nufin ku karkace karkacewa mai girma.

28. Allah Yana nufin Ya sassauta muku. Kuma an halicci ɗan’adam mai rauni ne.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gama bayanin wasu hukunce-hukuncen aure, sai kuma ya nuna cewa, yana nufin bayanan su zama shiriya da haske ga mutane, don su san hukunce-hukuncen shari’a dalla-dalla na halal da na haram. Wannan it ace hanyar bayin Allah na farko, waɗanda Allah ya yi musu ni’ima, su ne annabawa da mabiyansu. Allah kuma mai cikakken sani ne, ba abin da yake ɓuya gare shi, kuma mai hikima ne cikin duk shari’unsa da hukunce-hukuncensa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake nanata nufinsa na karɓan tuban bayinsa, kuma ya bayyana mugun nufi na ‘yan duniya, fasiƙai da kafirai, waɗanda ko da yaushe suke son ganin muminai sun saki hanyar gaskiya da tsoron Allah, sun bi tasu ta watsewa da saɓon Allah. Ya kuma nuna cewa, yana nufin

ya sassauta wa muminai cikin duk abin da ya shar'anta musu, saboda Musulunci addini ne da ya kafu a kan sauƙi ba tsanani ba; domin shi kuma ɗan'adam a ɗabi'arsa, Allah ya halicce shi mai rauni ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya ambaci kalmar 'dukiyoyinku', a ayar don ya nuna dukiya kamar mallakar kowa da kowa ce. Wannan faɗakarwa ce ga al'umma a kan su zama masu taimakon juna da dukiyoyinsu. Watau kamar Allah yana cewa ne, dukiyar ɗayanku dukiyar al'ummarku ce; idan mutum ya halatta wa kansa cin dukiyar ɗan'uwansa ba a kan gaskiya ba, to kamar ya halatta wa wani ne shi ma ya ci dukiyarsa ba a kan gaskiya ba, domin abin da ka yi ma wani kai ma za a yi maka.

2. Haramun ne a gudanar da wata mu'amala ta haramtaccen kasuwanci ko da kuwa da yardar ɓangarorin biyu ne, domin haramtacciyar mu'amala ita ma cin dukiya ne ba bisa gaskiya ba.

3. Duk wata yarjejeniya ta mu'amalar kasuwanci tana ƙulluwa ne ta hanyar yardar ɓangarorin mu'amalar, a aikace ne ko ta baka ko a rubuce, domin Allah ya sharɗanta yarda ne, don haka ta kowace hanya ta samu yarjejeniya ta ƙullu kenan.

4. An ambaci kasuwanci shi kaɗai a nan, domin shi ne mafi yawan hanyar neman dukiya.

5. Allah mahaliccin bawa ya fi tausayinsa fiye da yadda bawa yake tausayin kansa, don haka ya haramta masa ya kashe kansa da kansa.

6. Ambaton manyan laifuka ko kaba'ira a wannan wuri ya nuna laifuka kashi biyu ne, akwai manya, akwai kuma ƙanana, waɗanda aka kira su da *sayyi'at'.*

7. Duk sa'adda bawa ya nisanci manyan laifuka, to Allah ya yi alƙawarin kankare masa ƙananan; idan kuwa bai nisance su ba, to sai a kama shi da duka biyun.

Suratun Nisa'i (29-31)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَأۡكُلُوٓاْ أَمۡوَٰلَكُم بَيۡنَكُم بِٱلۡبَٰطِلِ إِلَّآ أَن تَكُونَ تِجَٰرَةً عَن تَرَاضٖ مِّنكُمۡۚ وَلَا تَقۡتُلُوٓاْ أَنفُسَكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِكُمۡ رَحِيمٗا ٢٩ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ عُدۡوَٰنٗا وَظُلۡمٗا فَسَوۡفَ نُصۡلِيهِ نَارٗاۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرًا ٣٠ إِن تَجۡتَنِبُواْ كَبَآئِرَ مَا تُنۡهَوۡنَ عَنۡهُ نُكَفِّرۡ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَنُدۡخِلۡكُم مُّدۡخَلٗا كَرِيمٗا ٣١

29. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ci dukiyoyinku a tsakaninku ta hanyar rashin gaskiya, sai dai in ya kasance kasuwanci ne bisa yarjejeniya a tsakaninku. Kuma kada ku kashe kawunanku. Lalle Allah Ya kasance Mai tausaya muku ne.

30. Kuma duk wanda ya aikata haka don ƙetare iyaka da zalunci, to za Mu shigar da shi cikin wata wuta; kuma yin haka ya kasance abu ne mai sauƙi a wurin Allah.

31. Idan har kun nisanci manya-manyan laifuffukan da aka hana ku, to za Mu kankare muku ƙananan kurakuranku, kuma za Mu shigar da ku wata mashiga ta karamci.

Bayan an gama bayani game da aure, sai kuma bayani a kan dukiya ya biyo baya, domin auren ana yin sa da dukiya ne, haka ma sayen ƙwarƙwara sai da dukiya. Bayan wannan kuma ayoyi da dama sun gabata

game da sha'anin dukiyoyin marayu da sha'anin rabon gado, duk wannan ta sa aka zo da bayani a kan hanyar da ta dace a nemi wannan dukiya da kuma wadda ba ta dace ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana muminai cin dukiyoyin 'yan'uwansu ba bisa haƙƙi ba, wato kamar ta hanyar caca ko riba ko ciniki irin wanda shari'a ta haramta, sai dai ta hanyar kasuwanci na halal, wanda aka gina shi a kan yarjejeniya, to wannan ya halatta.
Saboda kasancewar dukiya da rayuwa tare suke, sai bayan an hana cin dukiya ta hanyar ɓarna, sai Allah ya zo da bayanin haramta salwantar da rai ba da haƙƙi ba. Larabawa a lokacin jahiliyya yawancin dukiyoyinsu suna tara su ne ta hanyar fashi da makami ko kai hare-hare a kan jama'a da ƙwace musu dukiyoyinsu, wanda hakan sau tari yakan haifar da salwantar rayuka. Hakanan shi ma wanda za a ƙwatar masa dukiya ba tare da wani haƙƙi ba, yakan iya fusata ya nemi ƙwato dukiyarsa ta kowace irin hanya, wanda hakan ka iya kaiwa ga rasa rai. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana mutum ya kashe kansa da kansa, ko ya kashe ɗan'uwansa, domin duk wanda ya kashe ɗan'uwansa, kamar ya kashe kansa ne.

An karɓo daga Sabit ɗan Dhahhak (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Wanda duk ya kashe kansa da wani abu a duniya, to da shi za a yi masa azaba a lahira." [Bukhari #6047, da Muslim #110].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda duk ya kashe kansa da wani ƙarfe, to zai zo da wannan ƙarfen a hannunsa yana daba shi a cikinsa a wutar Jahannama ranar gobe ƙiyama, yana mai dawwama abin dawwamarwa a cikinta har abada. Wanda duk ya sha guba ya kashe kansa, to zai zo yana kwankwaɗar wannan gubar a cikin wutar Jahannama, yana mai dawwama abin dawwamarwa a cikinta har abada. Wanda ya jeho kansa daga ƙololuwar dutse ya kashe kansa, to zai yi ta gangarowa a cikin wutar Jahannama, yana mai dawwama abin dawwamarwa a cikinta har abada." [Muslim #109].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lalle shi mai rahama ne ga bayinsa, don haka ya haramta musu kashe kawunansu ko kashe junansu ba bisa wani haƙƙi ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi gargaɗi mai tsanani ga mai cin dukiyar jama'a ta hanyar zalunci da ƙetare iyaka, cewa makomarsa ita ce wutar Jahannama mai tsananin ƙuna, kuma azabtar da shi abu ne mai matuƙar sauƙi a wurin Allah, don babu wanda ya isa ya hana shi.
To bayan wannan gargaɗi kuma, sai Allah ya ambaci alƙawarinsa ga masu nisantar aikata alkaba'ira, ya bayyana musu cewa, idan har sun nisanci manyan laifuka, to shi kuma ya yi musu alƙawarin kankare musu ƙananan zunubbansu, daga ƙarshe kuma ya shigar da su gidan Aljanna, ya karrama su a cikinta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Musulunci ya hana mutum ya riƙa burin abin da aka fifita ɗan'uwansa da shi a kansa. Wannan burin daidai yake da hassada, hassada kuma haramun ce, in ban da a kan abubuwa biyu da Sunna ta bayyana, watau burin samin ilimi mai amfani irin na 'wane' da aiki da shi; ko samun dukiya ta halal irin ta 'wane' da ciyar da ita a inda ya dace. [Duba, Bukhari #5025, da Muslim #815].

2. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana bayinsa wani abu da suke so, sai ya buɗe musu wata ƙofar da ta fi masu amfani kuma mai sauƙin shiga da cim ma buƙata.

3. Yalwar falalar Ubangiji, shi ya sa ya umarce mu da mu roƙe shi falalarsa, ya kuma yi wannan umarni ne domin idan mun roƙe shi zai ba mu, shi kuma mai karamci ne.

4. Masu kira zuwa ga daidaita mace da namiji cikin kowane lamari, waɗannan suna jayayya ne da hukuncin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda ya bambanta su a halitta da ƙarfin jiki da zurfin hankali da hangen nesa, ya bambanta tsakaninsu a wasu hukunce-hukunce, kamar rabon gado. Ai Allah ba azzalumin kowa ne ba, da a ce yin haka zalunci ne, da ba zai yi ba. Don haka yarda da irin wannan da'awar bijire wa hukuncin Allah ne na ƙaddara da shari'a, sannan tuhumar sa ne da zalunci, wanda yin haka kafirci ne.

Suratun Nisa'i (32-33)

وَلَا تَتَمَنَّوْاْ مَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بِهِۦ بَعْضَكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍۚ لِّلرِّجَالِ نَصِيبٌ مِّمَّا ٱكْتَسَبُواْۖ وَلِلنِّسَآءِ نَصِيبٌ مِّمَّا ٱكْتَسَبْنَۚ وَسْـَٔلُواْ ٱللَّهَ مِن فَضْلِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمًا ٣٢ وَلِكُلٍّ جَعَلْنَا مَوَٰلِيَ مِمَّا تَرَكَ ٱلْوَٰلِدَانِ وَٱلْأَقْرَبُونَۚ وَٱلَّذِينَ عَقَدَتْ أَيْمَٰنُكُمْ فَـَٔاتُوهُمْ نَصِيبَهُمْۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ شَهِيدًا ٣٣

32. Kuma kada ku yi burin abin da Allah Ya fifita wasunku a kan wasu da shi, maza suna da kaso na abin da suka tsuwurwurta, haka mata ma suna da kaso na abin da suka tsuwurwurta. Kuma ku roƙi Allah daga falalarsa. Lalle Allah Ya kasance Masanin komai ne.

33. Kuma kowa Mun sanya masa magadansa daga abin da mahaifa suka bari ko dangi mafiya kusanci. Su kuma waɗanda rantsuwar ƙulla (zumunci) ta haɗa tsakaninku, to ku ba su rabonsu. Lalle Allah Ya kasance Mai tsinkaye ne a kan komai.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana cin dukiyar mutane ba a kan gaskiya ba, ya kuma hana kashe rai, sai a waɗannan ayoyi kuma ya hana mutum ya riƙa burin falalar da Allah ya fifita ɗan'uwansa da ita; yin hakan yakan haifar da hassada; ita kuma hassada tana iya kai mai ita ga cin dukiyar ɗan'uwansa ba bisa gaskiya ba, mai yiwuwa ma ta kai shi ga kisan kai. Abubuwan da Allah ya hana mutum ya ƙwallafa ransa a kansu sun haɗa da dukiya ko matsayi ko mulki da makamantansu. Allah kuma ya umarci mutane maza da mata, kowa ya yi aiki irin wanda ya dace da shi, na alheri ko na sharri, tabbas kuma zai ga sakamakon aikinsa, ba tare da an tauye masa komai ba. Amma Allah ya faɗakar da su cewa, su roƙe shi falalarsa, don shi ne mai bayarwa, kuma duk wanda yake da wata falala to shi ya ba shi ita. Allah kuma mai cikakken ilimi ne, ya san wanda ya cancanta ya ba wa, da wanda ya cancanta ya hana masa, kuma mai hikima ne wajen ajiye komai a muhallinsa da ya dace da shi.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wata mata ta zo wurin Annabi (ﷺ) ta ce: "Ya Annabin Allah, an ce kason namiji ɗaya daidai yake da kason mata guda biyu, kuma aka ce shaidar mace biyu daidai take da shaidar namiji ɗaya, to a wajen aiki ma haka muke? Idan mace ta yi aiki mai kyau sai a ba ta rabin ladan da za a ba namiji?" Sai wannan ayar ta sauka." [Ibn Abi Hatim, *At-Tafsir*#5223 da Al-Dhiya, *Mukhtarah* #115].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dawo a kan zancen gado, inda ya ce, kowane mutum ya sanya masa masu cin gadonsa na dukiyar da ya mutu ya bari daga mahaifinsa da mahaifiyarsa da sauran danginsa. Wasu malamai sun ce, ana nufin magada masu ci da asibci, kamar 'yan'uwansa da 'ya'yan baffanninsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce, waɗanda kuka ƙulla alƙawari da su da yarjejeniyar zumunta ta hanyar rantse-rantse masu ƙarfi a tsakaninku, to ku ba su kason su na gado.
Wannan gabar da dama daga cikin malaman tafsiri sun ce an shafe hukuncinta da ayar da take cikin *Anfali*, aya ta 75. Imam Ibn Jarir At-Tabari yana ganin hukuncinta yana nan ba a shafe shi ba, domin yana ganin tana magana ne a kan waɗanda suka ƙulla yarjejeniya ta ƙawance a kan za su taimaka wa juna; za

su yi wa juna nasiha, to wannan hukuncin yana nan, don haka a fahimtarsa ‘rabonsu’ da aka ambata, ana nufin nasiha da taimakon juna, ba gado ake nufi ba. [Dubi, Ibn Jarir, Juzu’i na 3, Shafi na 281].
An karƀo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: ‘Faɗar Allah: “Kuma kowa mun sanya masa magadansa.” Ibn Abbas ya ce: “Ana nufin magada.” Sannan faɗar Allah: “… waɗanda rantsuwar ƙulla (zumunci) ta haɗa tsakaninku.” Ibn Abbas ya ce: “Lokacin da masu hijira suka zo Madina, sai ya zamanto ɗaya daga cikinsu zai iya cin gadon mutumin Madina, ban da sauran danginsa na jini, saboda ‘yan’uwantakar da Annabi (ﷺ) ya haɗa a tsakaninsu. Yayin da Allah ya saukar da faɗarsa: “Kuma kowa mun sanya masa magadansa.” sai aka shafe wancan hukunci. Sannan Allah ya ce: “…waɗanda rantsuwar ƙulla (zumunci) ta haɗa tsakaninku.” Ibn Abbas ya ce: “Na taimako da agaji, amma an shafe na gado, sai dai idan ya yi masa wasiyya.” [Bukhari #4581].

Wannan yana nufin an shafe abin da ya danganci gado a tsakaninsu, amma abin da ya danganci taimakon juna, wannan yana nan ba a shafe shi ba.Sannan Allah ya bayyana cewa, shi mai tsinkaye ne kan komai, babu abin da ba ya ganin yadda yake gudana a cikin halittunsa kakaf.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Fifikon jinsin maza a kan jinsin mata.

2. Miji shi ne shugaba a gidansa.

3. Mace saliha tana bin dokokin Allah ne wajen tsare mutuncinta ba dokokin mijinta ba, saboda haka ko da ya yarda ta saɓa wa dokokin Allah saboda rashin riƙonsa da addini ko kuma don al’ummar da yake rayuwa a cikinsu sun yarda a saɓa wa waɗannan dokoki na Allah, to ba za ta yi masa biyayya ba a nan.

4. Bin matakan ladabtarwar da aka ambata ɗaya bayan ɗaya: Wa’azi, sannan ƙauracewa, sannan duka. Bai dace a yi amfani da na biyu ko na uku ba, sai idan na farko bai yi amfani ba, sannan sai a je na biyu, sannan na uku.

5. Karyata maganar masu cewa duka ba hanya ce ta ladabtarwa ba, wai hanya ce mai sanya zuciya ta ƙeƙashe. Wannan ayar ta ƙaryata haka, domin wanda ya shar’anta dukan shi ne wanda zukatan bayi suke hannunsa, yana juya su yadda ya ga dama.

6. Wajibi ne a kan masu hukunci tsakanin ma’aurata su zama masu kyakkyawar niyya, ba ƙoƙarin yardar da wani ɓangare ba.

7. Kyautata niyya yana sanyawa a samo dace daga Allah cikin dukkan al’amura.

8. Miji ne yake da iko da matarsa.

9. Haramun ne mace ta bijire wa mijinta.

10. Dole ne waɗanda za su zama mahukunta su kasance masu ilimin shari’ar Musulunci, domin marar ilimin ba zai san abin da yake daidai ya yi hukuncin da shi ba. Kuma wajibi ne su zama masu amana, domin wanda ba shi da amana ba za a amince masa ba.

11. Waɗannan mahukunta suna da damar su raba auren ta hanyar da ta dace idan sun gano ci gaba da zaman ma’auratan ba zai yiwu ba.

12. Nuni a kan cewa ya kamata duk wanda za a naɗa shi mai hukunci ga wata jama’a ya kasance ya san halayyar waɗannan jama’ar da ɗabi’unsu, shi ya sa a nan aka ce ‘daga danginsa da danginta’.

Suratun Nisa’i (34-35)

ٱلرِّجَالُ قَوَّٰمُونَ عَلَى ٱلنِّسَآءِ بِمَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بَعۡضَهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖ وَبِمَآ أَنفَقُواْ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡۚ فَٱلصَّٰلِحَٰتُ قَٰنِتَٰتٌ حَٰفِظَٰتٞ لِّلۡغَيۡبِ بِمَا حَفِظَ ٱللَّهُۚ وَٱلَّٰتِي تَخَافُونَ نُشُوزَهُنَّ فَعِظُوهُنَّ وَٱهۡجُرُوهُنَّ فِي ٱلۡمَضَاجِعِ وَٱضۡرِبُوهُنَّۖ فَإِنۡ أَطَعۡنَكُمۡ فَلَا تَبۡغُواْ عَلَيۡهِنَّ سَبِيلًاۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيّٗا كَبِيرٗا ٣٤ وَإِنۡ خِفۡتُمۡ شِقَاقَ بَيۡنِهِمَا فَٱبۡعَثُواْ حَكَمٗا مِّنۡ أَهۡلِهِۦ وَحَكَمٗا مِّنۡ أَهۡلِهَآ إِن يُرِيدَآ إِصۡلَٰحٗا يُوَفِّقِ ٱللَّهُ بَيۡنَهُمَآۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا خَبِيرٗا ٣٥

34. Maza su ne tsayayyu a kan mata saboda abin da Allah Ya fifita sashinsu da shi a kan sashi, kuma saboda abin da suka ciyar na dukiyarsu. To salihan mata masu ɗa’a ne, masu tsare (haƙƙoƙin mazajensu) ne a bayan idon mazajensu da tsarewar Allah. Waɗanda kuwa kuke jin tsoron kangarewarsu, to ku yi musu wa’azi, kuma ku ƙaurace musu a wuraren kwanciya, kuma ku doke su; amma idan sun yi muku ɗa’a, to kada ku nemi wata hanyar cutar da su. Lalle Allah Ya kasance Maɗaukaki ne, Mai girma.

35. Kuma idan kun ji tsoron ci gaba da samun saɓani a tsakaninsu, to sai ku aika da wani mai hukunci daga danginsa (mijin), da wani mai hukunci daga danginta (matar), in (su mahukuntan) suna nufin samar da gyara, to Allah zai daidaita tsakaninsu (ma’auratan). Lalle Allah Ya kasance Mai yawan sani ne Masanin abin da yake ɓoye.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, maza su ne suke da haƙƙin kula da matansu saboda abubuwa guda biyu:
Na farko, saboda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fifita jinsin maza a kan jinsin mata cikin abubuwa da dama, kamar ƙarfin jiki da kaifin hankali.
Na biyu, saboda su ne suke ɗaukar nauyin ciyarwa daga dukiyarsu, kuma wannan yana farawa tun daga lokacin da aka zo ɗaura aure; namiji shi ne mai biyan sadaki, sannan ya ci gaba da ɗaukar ɗawainiyar ci da sha da wurin zama na matarsa da abin da za ta haifa masa. Don haka matan da suka riƙe addininsu, suka bi Allah da Manzonsa (ﷺ), sannan suka yi wa mazajensu biyayya cikin duk abubuwan da ba su saba wa Allah ba, to waɗannan mata su ne masu kame mutuncinsu yayin da mazajensu ba sa nan, masu kulawa da dukiyoyin mazajensu, ba sa yi musu almubazzaranci ko ha’inci a ciki, saboda yadda Allah ya kiyaye su, ya ba su gamon-katar, ba wai yin su ba ne.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna mafita ga mazajen da suke tsoron kangarewar matansu ta hanyar yi musu tawaye. Ga hanyoyin da ya kamata su bi don magance abin tun da wuri:
Na farko, su tunatar da su Allah, su yi musu wa’azi, su tsoratar da su azabar Allah ga matar da take saba wa mijinta, sannan su umarce su da su bi Allah da Manzonsa don su sami rabauta a wurinsa.
Na biyu, idan wa’azinsu bai yi amfani ba, to sai su ƙaurace musu wajen kwanciya, ta hanyar juya musu baya ko da sun kwanta shimfiɗa ɗaya tare, ko kuma ta hanyar raba shimfiɗa.
Na uku, idan wannan hanyar ma ba ta yi amfani ba, to sai su ɗan doke su, duka ba mai raunana jiki ba, domin su ladabtu, su fahimci girman fusatar mazajensu a kansu.

An karɓo daga Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Haƙƙinku ne a kansu kada su bar wani ya hau muku shimfiɗarku; idan kuma har sun aikata hakan, to ku doke su duka ba mai raunanawa ba.” [Muslim #1218].

To idan matan sun saduda sun dawo ga yi wa mazansu biyayya, to kada su ci gaba da zarginsu a kan abin da ya riga ya wuce, ko su ce za su doke su bayan haka; su tuna cewa gaba da gabanta. Idan suna ganin su

ne sama da matansu, sun fi ƙarfinsu, to su sani Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sama da su, yana sama da kowa da komai, kuma mai girma ne a kan kowa da komai.
Sannan idan saɓanin da yake tsakanin ma'aurata ya ƙi ci ya ƙi cinyewa bayan mijin ya ɗauki waɗancan matakai guda uku ba su yi amfani ba, abin har yana so ya haifar da wata ɓaraka mai faɗi tsakaninsu, to sai a shirya zaman sulhu a tsakaninsu, a zaɓo mai hukunci daga ɓangaren mijin, a zaɓo wani daga ɓangaren matar, su zauna su duba matsalar, su yi wa tufkar hanci. Idan har masu sulhu sun zo ne da niyyar yin gyara, to Allah zai ba su dacewa ya zamana bakinsu ya haɗu a kan magana ɗaya da za ta dawo da komai daidai; su ma ma'auratan Allah zai ba su dace su dawo su ci gaba da zamantakewar aurensu cikin zaman lafiya da mutunta juna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman matsayin iyaye da wajabcin kyautata musu da guje wa ɓata musu rai.

2. Kyautata wa dangi.

3. Sukan wanda yake ɓoye falalar da Allah ya ba shi. Ɓoyewa iri biyu ce: Ɓoyewa a aikace ta hanyar ƙin nuna alamun ni'imar Allah tare da shi, kamar ya riƙa shiga marar kyau ko ya ƙi kyautata abincinsa da na iyalansa, da niyyar rowa da maƙo. Sai kuma ɓoyewa ta hanyar magana, ya ƙi ambaton ni'imar da Allah ya yi masa, sai dai kullum ya riƙa ƙorafi yana nuna wa mutane cewa shi matalauci ne, ko kawai rufin asiri ne yake da shi ba wadata ba.

4. Dole ne mutum ya riƙa auna aikin da zai yi, amfaninsa da cutarwarsa. Duk abin da zai cutar da imaninsa, ko ya jawo masa faɗawa cikin kafirci, to sai ya guje shi.

5. Duk mai ciyar da dukiyarsa, ya sani cewa dukiyar Allah ce da ya ara masa, idan ya ga dama yana iya ƙwacewa daga hannunsa, ya danƙa ta a hannun wani daban.

6. Wajabcin yin aiki da sunnar Annabi (ﷺ). Duk abin da ya inganta na umarnin Annabi (ﷺ) ko haninsa, dole ne Musulmi ya yi aiki da shi, ko da kuwa ba ya cikin Alƙur'ani.

Suratun Nisa'i (36-42)

*وَٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُشۡرِكُواْ بِهِۦ شَيۡـٔٗاۖ وَبِٱلۡوَٰلِدَيۡنِ إِحۡسَٰنٗا وَبِذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡجَارِ ذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡجَارِ ٱلۡجُنُبِ وَٱلصَّاحِبِ بِٱلۡجَنۢبِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِ وَمَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ مَن كَانَ مُخۡتَالٗا فَخُورًا ٣٦ ٱلَّذِينَ يَبۡخَلُونَ وَيَأۡمُرُونَ ٱلنَّاسَ بِٱلۡبُخۡلِ وَيَكۡتُمُونَ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦۗ وَأَعۡتَدۡنَا لِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٗا مُّهِينٗا ٣٧ وَٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمۡ رِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَلَا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَلَا بِٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۗ وَمَن يَكُنِ ٱلشَّيۡطَٰنُ لَهُۥ قَرِينٗا فَسَآءَ قَرِينٗا ٣٨ وَمَاذَا عَلَيۡهِمۡ لَوۡ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَأَنفَقُواْ مِمَّا رَزَقَهُمُ ٱللَّهُۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِهِمۡ عَلِيمًا ٣٩ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَظۡلِمُ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖۖ وَإِن تَكُ حَسَنَةٗ يُضَٰعِفۡهَا وَيُؤۡتِ مِن لَّدُنۡهُ أَجۡرًا عَظِيمٗا ٤٠ فَكَيۡفَ إِذَا جِئۡنَا مِن كُلِّ أُمَّةِۭ بِشَهِيدٖ وَجِئۡنَا بِكَ عَلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِ شَهِيدٗا ٤١ يَوۡمَئِذٖ يَوَدُّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَعَصَوُاْ ٱلرَّسُولَ لَوۡ تُسَوَّىٰ بِهِمُ ٱلۡأَرۡضُ وَلَا يَكۡتُمُونَ ٱللَّهَ حَدِيثٗا ٤٢

36. Kuma ku bauta wa Allah (Shi kaɗai), kada ku haɗa Shi da komai; kuma ku kyautata wa iyaye da dangi makusanta da marayu da talakawa da maƙwabci makusanci da maƙwabci na nesa, da abokin da ake tare da kuma matafiyi da bayinku. Lalle Allah ba Ya son duk wanda ya kasance mai taƙama, mai yawan fariya.

37. Su ne waɗanda suke rowa kuma suke umartar mutane da rowa kuma suke ɓoye abin da Allah Ya ba su na falalarsa. Mun kuwa yi tanadin azaba mai wulaƙantarwa ga kafirai.

38. Waɗanda kuma suke ciyar da dukiyoyinsu don mutane su gani, kuma ba sa yin imani da Allah, ba sa kuma yin imani da ranar ƙarshe. Duk wanda Shaiɗan ya kasance shi ne abokinsa, to tir da aboki irin wannan.

39. Kuma me zai cutar da su da a ce sun yi imani da Allah da ranar ƙarshe, kuma suka ciyar daga abin da Allah Ya arzurta su da shi? Kuma Allah Ya kasance Mai yawan sani ne gare su.

40. Lalle Allah ba Ya zalunci ko da daidai da nauyin jaririyar tururuwa; kuma idan ya kasance aiki ne mai kyau to zai ninka shi, kuma Ya ba da lada mai girma daga wurinsa.

41. To yaya al'amarin zai kasance idan Muka zo da kowace al'umma tare da mai yi mata shaida, kai kuma Muka zo da kai a matsayin mai shaida kan waɗannan al'ummar?

42. A wannan yini ne waɗanda suka kafirta kuma suka saɓa wa Manzo, za su yi burin ina ma a mayar da su ƙasa, kuma ba za su ɓoye wa Allah wani zance ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar bayinsa da su bauta masa shi kaɗai, kada su haɗa komai da shi cikin bauta. Kamar yadda ya umarce su da su kyautata wa mahaifa, ta hanyar yi musu biyayya a kan duk abin da bai saɓa wa Allah ba, da taimaka musu da abin da suke buƙata na rayuwa, da yi musu addu'a bayan mutuwarsu. Ya kuma yi umarni da kyautata wa dangi da marayu, waɗanda suka rasa iyayensu maza, kuma ba su balaga ba. Hakanan su kyautata wa mabuƙata, waɗanda ba sa samun abin da zai ishe su a rayuwa, hakanan maƙwabci wanda yake da dangantaka ta jini, da wanda ba shi da dangantaka ta jini da su.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Jibrilu bai gushe ba yana yi mini wasiyya da maƙwabci har sai da na yi zaton zai ce yana da gado." [Bukhari #6015, da Muslim #2625].

Hakanan ya yi umarni da su kyautata wa duk wani wanda tafiya ta haɗa su da shi, ko kuma wanda zama ya haɗa su da shi, kamar mata. Hakanan ya yi umarnin kyautatawa ga matafiyi wanda ya zo wucewa, da kuma bayinsu da suke ƙarƙashinsu.

An karɓo daga Khaisama (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Muna zaune tare da Abdullahi ɗan Umaru (Allah ya ƙara masa yarda), sai wani hadiminsa ya shigo, sai Abdullahi ya tambaye shi: "Shin ka ba wa bayin nan abincinsu?" Sai ya ce; "A'a." Sai ɗan Umaru ya ce: "Maza je ka ka ba su, domin Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Ya ishi mutum girman laifi, ya hana bawansa abincinsa." [Muslim # 996].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan hadimin ɗayanku ya kawo masa abincinsa, to idan har bai zaunar da shi sun ci tare ba, to ya ba shi loma ɗaya ko biyu, ko ci ɗaya ko biyu, domin shi ne ya tanadi wannan abincin." [Bukhari #2557].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "A mallaka wa bawa abincinsa da suturarsa, kada a ɗora masa aikin da ya fi ƙarfinsa." [Muslim #1662].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba ya son duk wani bawa mai ji-ji da kansa, mai yi wa mutane girman kai.An karɓo daga Iyadh (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Lalle Allah ya yi min wahayin cewa: ‘Ku zama masu tawali’u, kada ɗayanku ya riƙa yi wa wani alfahari, kada kuma wani ya zalunci wani.’ [Muslim #2865].

An karɓo daga Abu Malik Al-Ash’ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Abubuwa guda huɗu a cikin al’ummata suna daga ayyukan jahiliyya, kuma ba za su daina ba....” Daga cikinsu Annabi (ﷺ) ya ambaci alfahari da asali. [Muslim #934].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kashedi ga masu riƙe dukiyarsu suna rowar ta ga mabuƙata da yin aikin alheri, har ma kuma suna umartar wasu da su riƙa yin rowar dukiyarsu, kuma suna ɓoye dukiyar da Allah ya ni’imta su da ita don kada a san suna da ita a nemi taimakonsu, ko kada a zarge su da rowa, don haka ba sa barin wata alama a tare da su a tufafinsu ko a cimarsu ko muhallinsu ko abin hawansu. To masu irin wannan hali, Allah ya tanadar musu uƙuba ta wulaƙanci.
Yana daga cikin siffofin waɗannan mutane, har ila yau, idan sun ba da dukiyarsu, to suna yin haka ne don mutane su gani su yaba musu, ba don Allah suke yi ba. Ga su kuma imaninsu da Allah bai taka kara ya karya ba, balle su nemi kusanci da shi, kuma ba sa imani da ranar lahira, ballantana su yi kwaɗayin ladan cikinta. Shaiɗan ne yake tare da su yana ƙawata musu waɗannan munanan ayyuka. To duk wanda yake Shaiɗan ne abokinsa, yana masa biyayya a kan abin da yake umartar sa da shi, to lalle wannan aboki ya yi matuƙar muni.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci waɗannan masu rowar da dukiyarsu, kuma suna umartar wasu da yin rowa, da cewa me, zai cutar da su idan sun yi imani da Allah, kuma sun ciyar daga dukiyar da Allah ya ba su? Kuma Allah masani ne game da halin waɗannan mutane.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, ba ya zaluntar kowa cikin bayinsa da kowane irin nau’i na zalunci. Hasali ma idan mutum ya yi aiki na ƙwarai guda ɗaya, to zai ninka masa ladansa, kuma ya ba shi wani sakamako mai girma daga wurinsa, watau gidan Aljanna da abin da ta ƙunsa na ni’ima.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk abin da zai wakana a ranar alƙiyama, zai wakana ne da shaidar manzannin Allah. Domin Allah zai fito wa kowace al’umma da annabinta ya yi mata shaida, ya tabbatar da cewa, ya isar musu da saƙon Allah; ita ma wannan al’umma ta Annabi Muhammadu (ﷺ), zai zo ya ba da shaida a kansu cewa, ya isar musu da saƙon Allah.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce masa: “Karanta mini Alƙur’ani.” Sai ɗan Mas’ud ya ce: “Ni zan karanta maka Alƙur’ani, alhali kai aka saukar wa da shi?” Annabi (ﷺ) ya ce: “Duk da haka.” Sai na karanta masa Suratun Nisa’i, har sai da na zo daidai faɗarsa (Mai tsarki da ɗaukaka): “To yaya al’amarin zai kasance idan muka zo wa kowace al’umma da mai mata shaida, kai kuma muka zo da kai a matsayin mai shaida a kan waɗannan?” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Ya ishe ka haka.” Sai na waiwaya na kalle shi, sai na ga idanuwansa suna zubar da hawaye.” [Bukhari #5050].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da zai faru a wannan ranar da cewa, waɗanda suka kafirce wa Allah, kuma suka saba wa wannan Manzo nasa, za su yi burin ina ma a daidaita su da ƙasa, wato ta haɗiye su, a binne su a cikinta, su zama ƙasa, domin su tsira daga fuskantar hisabi. Alhali kuwa ba su isa su ɓoye wa Allah komai ba daga ayyukansu da maganganunsu, za su fito su yi iƙirari da laifukansu. Idan ma harsunansu sun ƙi su furta laifukansu, to gaɓoɓinsu ne za su bayyana komai da komai, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa a *Suratu Ya Sin*, aya ta 65.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin salla da wajabcin kula da ita.

2. Kwaɗaitarwa a kan halarto da zuciya yayin salla har masallaci ya san abin da yake faɗa.

3. Ba a la’akari wajen hukunci da maganar wanda yake cikin maye, ko da abin da zai faɗa kafirci ne, to ba za a kafirta shi ba.

4. Wucewa ta cikin masallaci ba daidai yake da zama a cikinsa ba wajen hukunci.

5. Abin da yake wajibi a kan mai janaba shi ne wanka, amma alwala wannan mustahabbi ce a gare shi.

6. Idan mai janaba ya yi wanka, ya halatta ya yi salla, ba sai ya sake alwala ba.

7. Matafiyin da ya rasa ruwa zai yi taimama ne lokacin da salla ta riske shi, ba zai jira har sai ya shigo gari ba.

8. Halaccin yin taimama daga duk wani abu da yake a doron ƙasa, kamar rairayi ko tsakuwa ko turɓaya ko taɓo ko daɓe da sauransu.

9. Mai taimama ba sai ya shafi sangalin hannunsa ba; zai wadatu ne kawai da shafar tafukan hannayensa kamar yadda sunna ta nuna.

Suratun Nisa’i (43)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقۡرَبُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنتُمۡ سُكَٰرَىٰ حَتَّىٰ تَعۡلَمُواْ مَا تَقُولُونَ وَلَا جُنُبًا إِلَّا عَابِرِي سَبِيلٍ حَتَّىٰ تَغۡتَسِلُواْۚ وَإِن كُنتُم مَّرۡضَىٰٓ أَوۡ عَلَىٰ سَفَرٍ أَوۡ جَآءَ أَحَدٞ مِّنكُم مِّنَ ٱلۡغَآئِطِ أَوۡ لَٰمَسۡتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَلَمۡ تَجِدُواْ مَآءٗ فَتَيَمَّمُواْ صَعِيدٗا طَيِّبٗا فَٱمۡسَحُواْ بِوُجُوهِكُمۡ وَأَيۡدِيكُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَفُوًّا غَفُورًا ٤٣

43. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kusanci salla alhalin kuna cikin maye har sai kun san abin da kuke faɗa, haka mai janaba, sai dai in masu ƙetara hanya ne, har sai kun yi wanka. Idan kuma kun kasance marasa lafiya ko a halin tafiya, ko ɗaya daga cikinku ya dawo daga bahaya ko kuma kuka sadu da mata kuma ba ku sami ruwa ba, to sai ku nufi doron ƙasa mai tsarki ku yi taimama, sai ku shafi fuskokinku da hannayenku. Lalle Allah Ya kasance Mai afuwa ne, Mai gafara.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga muminai cewa, kada su kusanci salla, watau kada su shige ta alhali suna cikin halin maye, har sai sun wartsake.

An karɓo daga Ali ɗan Abu Talib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Abdurrahman ɗan Auf ya shirya mana abinci, ya gayyace mu, ya ba mu giya muka sha, har muka bugu, sai lokacin salla ya yi, sai suka sa ni limanci, sai na karanta *Suratul Kafirun* kamar haka: “Ya ku kafirai, ba zan bauta wa abin da kuke bauta wa ba, mu kuma nuna bautar abin da kuke bauta wa.” Sai Allah ya saukar da faɗarsa: “Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kusanci salla alhalin kuna cikin maye, har sai kun san abin da kuke faɗa.” [Tirmizi #3026].

Wannan ayar an shafe ta da ayar da ta haramta giya gaba ɗaya da ke cikin *Suratul Ma’idah*, aya ta 90. Haka kuma Allah ya hana su salla, ko shiga masallaci lokacin da suke cikin halin janaba, har sai sun yi wanka, sai dai wanda wucewa ya zo yi ta ciki ba zama ba. Amma ga wanda yake rashin lafiya, ba zai iya amfani da ruwa ba, ko matafiyi da ya rasa ruwa, ko wanda ya yi bawali ko bahaya, ya rasa ruwan wanka, to hukuncinsa shi ne ya yi taimama a doron ƙasa mai tsarki, ya shafi fuskarsa da tafukan hannayensa.

An karɓo daga A'isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: "Mun fita tare da Manzon Allah (ﷺ) a ɗaya daga cikin tafiye-tafiyensa, sai da muka isa wata sahara, ko wani wuri mai suna Zatul Jaishi, sai abin wuyana ya tsinke ya faɗi, sai Manzon Allah (ﷺ) ya tsaya neman sa, kuma ba ruwa tare da su. Sai sahabbai suka je wurin Abubakar suka ce: 'Ba ka ga abin da A'isha ta yi ba, ta dakatar da Annabi (ﷺ) da sauran mutane, ga shi kuma ba ruwa tare da su?' Sai Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya zo ya same ni, Annabi (ﷺ) ya ɗora kansa a kan cinyata yana barci, sai ya ce: 'Kin dakatar da Annabi (ﷺ) tare da mutane, alhalin ba sa kusa da ruwa, kuma ba ruwa tare da su.' Sai A'isha ta ce: "Sai Abubakar ya yi mini faɗa, ya faɗi abin da Allah ya ba shi damar faɗa, ya riƙa zungurin kwankwasona da hannunsa, ni kuma na kasa motsi saboda Manzon Allah (ﷺ) yana kwance a cinyata. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya wayi gari ba ruwa tare da shi, sai Allah ya saukar da ayar taimama, suka yi taimama." Sai Usaidu ɗan Hudhairu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Ba wannan ce farkon albarkarku ba, ya iyalan gidan Abubakar." Ai'sha ta ce: "Sai muka tashi raƙumin da nake kansa, sai ga abin wuyan a ƙarƙashinsa." [Bukhari #334, da Muslim #367].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, shi mai afuwa ne, mai gafara ga zunubban bayinsa da gajiyawarsu.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi a kan sharrin Yuhudawa da Nasara da makircinsu ga Musulmi.

2. Daga cikin mutane akwai wanda Allah zai ba shi wani rabo na ilimi, amma sai ya take shi, ya zaɓi ɓata a kan shiriya, ya fifita ƙarya a kan gaskiya. To masu irin wannan sifa a cikin malamai, sun yi kama da malaman Yahudawa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rarrashin muminai da kwantar musu da hankali, yana nuna musu cewa, ya fi su sanin maƙiyansu, don haka shi ne zai yi musu maganinsu, ya kare su daga sharrinsu da makircinsu.

4. Dole ne Musulmi su fahimci cewa, suna da maƙiya, don haka su riƙa yin hattara a koyaushe.

5. Ana kama mutum ne bisa ga niyyarsa, don haka ko da mutum zai yi kyakkyawar magana a zahiri, amma a ɓoye yana nufin wata mummunar ma'ana, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai kama shi da wannan niyyar tashi.

6. Duk wanda ya hana wani mummunan aiki, to yana da kyau ya kawo wani kyakkyawa madadinsa da za a yi aiki da shi.

7. Waɗanda suke jirkita maganar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta hanyar ba ta wata ma'ana da ta yi daidai da son zuciyarsu, waɗannan suna kwaikwayon Yahudawa ne.

8. Bayanin taurin kan Yahudawa da ƙullatarsu ga Annabi (ﷺ) da nuna masa girman kai.

9. Sukan addini da masu yin sa ɗabi'a ce ta Yahudawa.

10. Duk wanda Allah ya la'ance shi, to wannan ba zai iya gane gaskiya ba, domin za ta birkice masa, ya riƙa yi mata kallon ƙarya, don haka ba zai taɓa bin hanyar alheri ba.

11. Kafirci shi ne yake jawo wa mutum tsinuwar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratun Nisa’i (44-46)

أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ أُوتُواْ نَصِيبٗا مِّنَ ٱلۡكِتَٰبِ يَشۡتَرُونَ ٱلضَّلَٰلَةَ وَيُرِيدُونَ أَن تَضِلُّواْ ٱلسَّبِيلَ ٤٤ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِأَعۡدَآئِكُمۡۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَلِيّٗا وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ نَصِيرٗا ٤٥ مِّنَ ٱلَّذِينَ هَادُواْ يُحَرِّفُونَ ٱلۡكَلِمَ عَن مَّوَاضِعِهِۦ وَيَقُولُونَ سَمِعۡنَا وَعَصَيۡنَا وَٱسۡمَعۡ غَيۡرَ مُسۡمَعٖ وَرَٰعِنَا لَيَّۢا بِأَلۡسِنَتِهِمۡ وَطَعۡنٗا فِي ٱلدِّينِۚ وَلَوۡ أَنَّهُمۡ قَالُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَا وَٱسۡمَعۡ وَٱنظُرۡنَا لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۡ وَأَقۡوَمَ وَلَٰكِن لَّعَنَهُمُ ٱللَّهُ بِكُفۡرِهِمۡ فَلَا يُؤۡمِنُونَ إِلَّا قَلِيلٗا ٤٦

44. Shin ba ka ga waɗannan da aka ba su wani rabo na ilimin Littafi ba, suna sayen ɓata, kuma suna nufin su ga kun ɓace daga kan hanya?

45. Allah kuma Shi ne mafi sanin maƙiyanku. Kuma Allah Ya isa Ya zama majiɓinci (gare ku), kuma Ya isa Ya zama Mai taimako (gare ku).

46. Cikin waɗanda suka zama Yahudawa akwai waɗanda suke juyar da kalmomi daga bigirensu, kuma suna cewa: “Mun ji, kuma mun saba, kuma ka saurara, kai ba abin a saurare ka ba ne, kuma *ra’ina*’.” Suna masu karkatar da harashensu kuma don su soki addini. Da za su ce: “Mun ji, mun yi ɗa’a, kuma ka saurare mu, kuma ka jira mu.” da ya kasance mafi alheri gare su, kuma ya fi zama miƙaƙƙiyar (hanya), sai dai Allah Ya riga Ya tsine musu saboda kafircinsu, ba za su yi imani ba sai kaɗan.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gaya wa Annabinsa (ﷺ) cewa, shin bai ga Yahudawa da Nasara ba, waɗanda Allah ya ba su wani rabo na ilimi, amma kuma suna zaɓar ɓata maimakon shiriya, sannan suna son ganin su ma muminai sun ɓace sun bar hanyar shiriya? Allah kuma shi ya fi sanin maƙiyansu, don haka shi ne zai kare su daga sharrinsu da makircinsu, ya ba su nasara a kansu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Manzonsa (ﷺ) halin Yahudawa masu canza ayoyin Attaura, ko su canza musu ma’anoni. Kuma idan sun zo wurin Annabi (ﷺ), sai su riƙa yi masa gatse suna cewa: “Mun ji abin da kake faɗa, amma ba za mu bi ba;” su riƙa nuna masa rashin ladabi, suna cewa: “Ka saurare mu, Allah ya kurumtar da kai, ya hana ka ji,” suna zagin sa da waɗansu maganganu, suna ce masa ‘ra’ina’, wato kamar suna nufin: “Ka ba mu jinka,” amma ba haka suke nufi ba; suna karkatar da harshensu ne da wata mummunar ma’ana, watau ‘daƙiƙi’ da harshensu. Manufarsu kawai ita ce sukan addinin Musulunci, ta hanyar yi wa Annabi (ﷺ) shaƙiyanci.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Yahudawan cewa, ai da kamata ya yi su ce: “Mun ji kuma mun bi, kuma ka saurare mu, ka dakace mu don mu fahimci abin da kake faɗa mana,” domin faɗar haka ita ce ta fi musu alheri, kuma ta fi zama miƙaƙƙiyar magana. To amma ina! Ba za su faɗi haka ba, saboda Allah ya riga ya tsine musu, ya nisanta su daga rahamarsa saboda kafircinsu, ba sa yin imani sai ɗan kaɗan wanda ba zai amfana musu komai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur’ani ya zo yana gaskata littattafan da suka gabace shi, amma ya shafe duk hukunce-hukuncensu, sai abin da ya zo da shi.

2. Kaɗaita Allah da bauta masa shi ne ginshiƙin addini. Allah ba ya karɓar aikin mutumin da ba shi da Tauhidi, kuma ba ya gafarta masa idan ya mutu yana shirka.

3. Duk wani saɓon Allah wanda bai kai shirka ba, Allah yana iya gafarta shi ga wanda ya ga dama. Don haka mai aikata laifin da bai kai shirka ba, ba shi da tabbas na cewa, Allah zai gafarta masa; wannan

kaɗai ya isa ya sa mai hankali ya guji saɓa wa Allah, domin Allah yana iya kama shi da wannan laifi, ya ƙi gafarta masa.

4. Wannan ayar tana nuna Bayahude ma mushiriki ne, domin in da ba haka ba ne, to da ya shiga cikin rukunin waɗanda za a iya yi wa gafara. Kuma alaƙar wannan ayar da wadda ta gabata shi ne gargaɗi ga Yahudawa da su bar abin da suke kai domin shirka ce wadda Allah ba zai gafarta musu ba idan har suka mutu ba su tuba ba.

5. Akwai raddi ga Mu'utazilawa da Khawarijawa, masu cewa, duk wanda ya mutu yana saɓon Allah, bai tuba ba, to Allah ba zai gafarta masa ba.

6. Hakanan ayar tana mayar da martani ga Murji'a masu cewa, Musulmi masu laifuka manya ba za a yi musu azaba ba, don Allah cewa ya yi 'ga wanda ya ga dama'.

Suratun Nisa'i (47-48)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ ءَامِنُواْ بِمَا نَزَّلۡنَا مُصَدِّقٗا لِّمَا مَعَكُم مِّن قَبۡلِ أَن نَّطۡمِسَ وُجُوهٗا فَنَرُدَّهَا عَلَىٰٓ أَدۡبَارِهَآ أَوۡ نَلۡعَنَهُمۡ كَمَا لَعَنَّآ أَصۡحَٰبَ ٱلسَّبۡتِۚ وَكَانَ أَمۡرُ ٱللَّهِ مَفۡعُولًا ٤٧ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱفۡتَرَىٰٓ إِثۡمًا عَظِيمًا ٤٨

47. Ya ku waɗanda aka ba su littafi, ku yi imani da abin da Muka saukar mai gaskata abin da yake tare da ku, tun kafin Mu shafe wasu fuskoki, Mu mayar da su bayansu, ko kuma Mu la'ance su irin yadda Muka la'anci ma'abota ranar Asabar. Kuma al'amarin Allah ya kasance abin zartarwa ne.

48. Lalle Allah ba Ya gafarta a yi shirka da Shi, amma Yana gafarta abin da bai kai shirka ba ga wanda Ya ga dama. Kuma duk wanda ya yi shirka da Allah, to haƙiƙa ya ƙirƙiri wani gagarumin laifi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana jan kunnen Yahudawa da Nasara ne, waɗanda ya saukar musu da littafin Attaura da Linjila, da lalle su yi imani da Alƙur'ani wanda ya saukar wa Annabinsa Muhammad (ﷺ), wanda kuma ya ƙunshi abin da yake gaskata littattafan da aka saukar musu, tun kafin ya shafe fuskokinsu, ya mayar musu da su bayansu, ko kuma ya kore su daga rahamarsa, ya azabtar da su, kamar yadda ya yi wa ma'abota ranar Assabar; watau waɗanda aka hana su kamun kifi ranar Asabar, sai suka riƙa yin ɗabara suna kamun kifi a ranar, sai Allah ya mayar da su birrai, kamar yadda ya ambata a *Suratul Baƙara*, aya ta 154, da *Suratul A'araf* aya ta 163-166. Kuma idan al'amarin Allah ya zo, to ba makawa sai ya tabbata.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba zai gafarta wa duk wanda ya yi shirka, watau ya haɗa wani da shi a wajen bauta ba, amma yana gafarta abin da bai kai shirka ba ga wanda ya ga dama. Duk wanda ya yi shirka, to haƙiƙa ya tafka babban laifi.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: Allah mai girma da buwaya yana cewa: "Duk wanda ya haɗu da ni da kimanin cikin ƙasa na laifuka, sannan ba ya haɗa wani da ni wajen bauta, to zan haɗu da shi da kimanin cikin ƙasa na gafara." [Muslim #2687].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na tambayi Annabi (ﷺ): "Wane zunubi ne ya fi girma a wurin Allah?" Sai ya ce: "Ka sanya wa Allah kishiya, alhali shi ya halicce ka." Sai na ce: "Lalle wannan babban abu ne...." [Bukhari #4477 da Muslim #86].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin mutum ya riƙa tsarkake kansa da kansa.

2. Ba laifi wani ya tsarkake wani, ta hanyar bayanin abin da ya sani nasa na alheri, ba kawai da son zuciya ba.

3. Bayanin cewa, waɗannan masu yin hassadar su ma Allah Ta'ala ya yi musu tasu falalar, bai bar su hakanan ba, to don me suke yi wa wasu hassada don an ba su wata falala? Don haka yana daga cikin maganin hassada, mutum ya dubi falalar da shi Allah ya yi mishi.

4. Munin aikin Yahudawa. Ga shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su wani kaso na ilimin littafi, amma duk da haka suka fito suna cewa, wai mushirikai masu bautar gumaka sun fi Annabi da sahabbansa da muminai zama a kan shiriya. Hukuncin wanda ya san gaskiya ya ƙi bin ta, ya fi muni a kan wanda bai san ta ba tun farko.

5. Kuskure ne Musulmi ya riƙa cewa kafirai sun fi Musulmi gaskiya ko amana ko cika alƙawari da sauransu. Duk Musulmin da yake faɗar haka, to ya yi koyi ne da Yahudawa. Idan har akwai rashin gaskiya a cikin Musulmi, ko ha'inci ko rashin cika alƙawari da sauransu, to sun fi yawa da muni a cikin waɗanda ba Musulmi ba. Duk wata kyakkyawar ɗabi'a ta waɗanda ba Musulmi ba, to akwai irinta ko fiye da ita a cikin Musulmi.

6. Ba a yi wa mutum hassada sai idan akwai wata falala tare da shi. Duk sa'adda ya sami cikakkiyar falala, to hassada da za a yi masa sai ta fi yawa. Babu wata falala da ta kai annabci, don haka masu yi wa Annabi (ﷺ) hassada suke da yawa, kuma hassadarsu ta fi ƙarfi.

7. Yadda ake yi wa mai kuɗi da mulki hassada, haka ake yi wa mai ilimi ko mai martaba ko mai addini hassada.

Suratun Nisa'i (49-57)

أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ يُزَكُّونَ أَنفُسَهُمْۚ بَلِ ٱللَّهُ يُزَكِّي مَن يَشَآءُ وَلَا يُظْلَمُونَ فَتِيلًا ﴿٤٩﴾ ٱنظُرْ كَيْفَ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَۖ وَكَفَىٰ بِهِۦٓ إِثْمًا مُّبِينًا ﴿٥٠﴾
أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ أُوتُواْ نَصِيبًا مِّنَ ٱلْكِتَٰبِ يُؤْمِنُونَ بِٱلْجِبْتِ وَٱلطَّٰغُوتِ وَيَقُولُونَ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ هَٰٓؤُلَآءِ أَهْدَىٰ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ سَبِيلًا ﴿٥١﴾
أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُۖ وَمَن يَلْعَنِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ نَصِيرًا ﴿٥٢﴾ أَمْ لَهُمْ نَصِيبٌ مِّنَ ٱلْمُلْكِ فَإِذًا لَّا يُؤْتُونَ ٱلنَّاسَ نَقِيرًا ﴿٥٣﴾ أَمْ يَحْسُدُونَ
ٱلنَّاسَ عَلَىٰ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦۖ فَقَدْ ءَاتَيْنَآ ءَالَ إِبْرَٰهِيمَ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَءَاتَيْنَٰهُم مُّلْكًا عَظِيمًا ﴿٥٤﴾ فَمِنْهُم مَّنْ ءَامَنَ بِهِۦ وَمِنْهُم
مَّن صَدَّ عَنْهُۚ وَكَفَىٰ بِجَهَنَّمَ سَعِيرًا ﴿٥٥﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِنَا سَوْفَ نُصْلِيهِمْ نَارًا كُلَّمَا نَضِجَتْ جُلُودُهُم بَدَّلْنَٰهُمْ جُلُودًا غَيْرَهَا لِيَذُوقُواْ
ٱلْعَذَابَۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَزِيزًا حَكِيمًا ﴿٥٦﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَنُدْخِلُهُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًاۖ لَّهُمْ
فِيهَآ أَزْوَٰجٌ مُّطَهَّرَةٌۖ وَنُدْخِلُهُمْ ظِلًّا ظَلِيلًا ﴿٥٧﴾

49. Shin ba ka ganin waɗannan da suke tsarkake kawunansu? Ba haka ba ne, Allah ne Yake tsarkake wanda Ya ga dama, kuma ba za a zalunce su ba ko da gwargwadon zaren ƙwallon dabino ne.
50. Duba ka ga yadda suke ƙirƙirar ƙarya su jingina wa Allah; kuma yin haka kaɗai ya isa zama wani zunubi mabayyani.

51. Shin ba ka ganin waɗanda aka ba su wani rabo na ilimin Littafi, suna yin imani da *Jibtu* da *Ɗagutu*, kuma suna faɗa wa waɗanda suka kafirta cewa: “Waɗannan su suka fi waɗanda suka yi imani shiriya.”?

52. Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya la’ance su; duk kuwa wanda Allah Ya la’anta, to ba za ka taɓa sama masa wani mataimaki ba.

53. Shin suna da wani kaso ne na mulki? To da haka ne da kuwa ba za su ba wa mutane ko da gwargwadon ɗigon bayan dabino ba.

54. Shin yanzu za su riƙa yi wa mutane hassada ne a kan abin da Allah Ya ba su na falalarsa? To haƙiƙa Mun bai wa zurriyar gidan Ibrahimu Littafi da kuma hikima, kuma Mun ba su wani mulki mai girma.

55. To daga cikinsu akwai wanda ya yi imani da shi, kuma daga cikinsu akwai wanda ya bijire masa. Jahannama kuwa ta isa wurin ƙuna.

56. Lalle waɗanda suka kafirce wa ayoyinmu, za Mu shigar da su wata wuta, duk lokacin da fatunsu suka ƙone, sai Mu musanya musu da wasu fatun daban, don su ɗanɗani azaba. Lalle Allah Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima.

57. Waɗanda suka yi imani kuwa, kuma suka yi aiki nagari, to za Mu shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu har abada; suna da mata tsarkaka a cikinsu; kuma za Mu shigar da su cikin wata inuwa, inuwa mayalwaciya marar gushewa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, kada ya yi mamakin waɗannan Yahudawa da Nasara da ire-irensu, waɗanda suke yabon kawunansu, suna wanke kansu daga laifuka, tare da cewa ba haka al’amarin yake ba, Allah ne kaɗai yake yabon waɗanda ya ga dama daga cikin bayinsa waɗanda suka cancanci yabo. Kuma shi Allah ba ya zaluntar bayinsa da komai duk ƙanƙantarsa. Dubi yadda waɗannan masu yabon kawunansu suke ƙagar ƙarya su jingina wa Allah. Ba shakka wannan laifi ne bayyananne.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake ce wa Annabinsa, ashe ba zai yi mamakin halin Yahudawa ba waɗanda Allah ya ba su wani kaso na ilimin Attaura, amma kuma suna yin imani da *Jibtu*, shi ne duk wani abu marar amfani a addini, kamar sihiri da canfi da makamantansu? Hakanan suna yin imani da *Ɗagutu*, shi ne duk abin da bawa ya ƙetare iyakokin Allah ta dalilinsa, kamar wani abin bauta ko wani shugaba ko wani abin yi wa biyayya. Sannan kuma waɗannan Yahudawa su ne suke faɗa wa kafirai cewa, wai hanyar da suke a kai ta fi hanyar da muminai suke a kai zama hanyar shiriya, wato dai a wajensu mushrikai sun fi muminai bin hanyar shiriya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir da masu wannan da’awar kuma ya la’ance su. Duk kuma wanda Allah ya la’ance shi, to ba za ka taɓa sama masa mai taimakon sa ko ya jiɓinci al’amarinsa ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da Ka’abu ɗan Ashrafu ya je Makka, sai Kuraishawa suka ce masa: “Kai ne ka fi kowa a Madina, kuma kai ne shugabansu.” Sai ya ce: “Haka ne.” Sai suka ce: “Shin ba ka ga wannan mutumin mai yankakken baya ba (watau wanda ba shi da ‘ya’ya) yana da’awar cewa ya fi mutanensa, alhalin mu ne masu kula da alhazai, mu ne masu hidimar ɗakin Ka’aba?” Sai aka saukar da ayar: “Lalle maƙiyinka shi ne mai yankakken baya.” Da kuma faɗar Allah: “Shin ba ka ga waɗanda aka ba wani rabo na littafi ba suna yin imani da *Jibtu* da *Ɗagutu*....” har zuwa ƙarshen aya ta 52. [Nasa’i, *As-Sunana Al-Kubra* #11643].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cewa, shin waɗannan Yahudawan suna da wani kaso ne na mulkin Allah da ya danƙa a hannunsu, wanda har za su fifita wanda suka ga dama da soye-soyen zukatansu, har kuma su iya hana Annabi (ﷺ) da sahabbansa wannan matsayi, su ba da shi ga waɗanda suke kafirai? Ma'ana dai, babu irin wannan rabon a hannunsu da za su iya yin wannan aika-aika. Domin da a ce wannan rabon mulki a hannunsu yake, da ba za su iya ba wa mutane ko da ɗan kaɗan ba, saboda tsananin rowarsu. Ko kuma abin da ya sa su irin wancan hukunci shi ne hassadarsu ga Annabi (ﷺ) da sahabbansa a kan annabcin da Allah ya ba shi, ga shi kuma Balarabe, ba daga gidan Banu Isra'ila ba. Me ya sa za su riƙa yi masa hassada, tare da cewa ba wannan ce farkon falalar da Allah yake yi wa bayinsa ba? Sun manta ne cewa, Allah ya ba wa kakanninsu daga cikin zurriyyar Annabi Ibrahim falala, ya ba su annabta, ya saukar musu da littattafai da hikima, kuma ya ba su mulki mai girman gaske, kamar irin wanda ya ba wa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi)? To amma duk da haka daga cikin ma'abota Littafi akwai wanda ya yi imani da Annabi (ﷺ) da Alƙur'anin da ya zo da shi, daga cikinsu kuma akwai wanda bai yi imani ba, kuma ya riƙa kange mutane yana hana su yin imani. To su sani cewa, azabar wuta mai ruruwa ta ishe su; Allah zai shigar da kafirai wutar Jahannama inda za a babbake su a cikinta. Duk sa'adda fatun jikinsu suka ƙone, sai Allah ya canza musu wasu fatun daban, domin su ci gaba da ɗanɗanar raɗaɗin azaba madawwamiya. Lalle Allah ya tabbata Gagara-badau ne, Gwani, mai hikima.
To amma kuma waɗanda suka yi imani, kuma suka yi kyawawan ayyuka, Allah zai shigar da su gidajen Aljanna, waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su ci gaba da zama a cikinsu har abada, kuma ni'imar da suke ciki ba mai yankewa ba ce har abada. Suna da matan aure tsarkaka a cikin waɗannan gidaje, kuma Allah zai shigar da su wata inuwa marar gushewa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Waɗannan ayoyi biyu su ne ginshiƙai na kafa gwamnatin Musulunci, ko da ba a saukar da komai na Alƙur'ani ba, su kaɗai da sun wadatar da Musulmi ta wannan ɓangaren, domin bayar da amana ga masu ita da hukunci tsakanin mutane da adalci, su ne jigon jagoranci na adalci a siyasa ta kyakkyawan shugabanci.

2. Umarni da yin hukunci na adalci. Adalci kuwa shi ne shari'ar Allah wadda ya saukar wa Annabinsa (ﷺ). Duk wanda ya yi hukunci da shari'a, to lalle ya yi adalci, wanda ya ƙi hukunci da ita, to bai yi adalci ba.

3. An yi umarni a nan da yi wa mutane adalci, kowa da kowa, Musulmi da kafiri, aboki da maƙiyi, ɗan'uwa da wanda ba ɗan'uwa ba.

4. Mayar da hukunci zuwa ga Allah shi ne komawa ga Alƙur'ani, mayar da shi kuma zuwa ga Manzon Allah (ﷺ) shi ne zuwa wajensa lokacin rayuwarsa da komawa ga sunnarsa bayan rasuwarsa.

5. Dole ne wajen bayanin hukunci na shari'a a haɗa Alƙur'ani da sunna wuri guda ba rarrabawa, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa su a nan. Wanda ya yi da'awar riƙo da Alƙur'ani shi kaɗai, ba tare da sunna ba, to ya kauce wa hanyar shiriya.

6. Idan ana jayayya a kan wani hukunci na shari'a, to nassi daga Alƙur'ani ko hadisi shi ne ke raba gardama, ba ra'ayin riƙau na wani malami ko shehi ba.

Suratun Nisa’i (58-59)

*إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُكُمۡ أَن تُؤَدُّواْ ٱلۡأَمَٰنَٰتِ إِلَىٰٓ أَهۡلِهَا وَإِذَا حَكَمۡتُم بَيۡنَ ٱلنَّاسِ أَن تَحۡكُمُواْ بِٱلۡعَدۡلِۚ إِنَّ ٱللَّهَ نِعِمَّا يَعِظُكُم بِهِۦٓۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ سَمِيعَۢا بَصِيرٗا ٥٨ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنكُمۡۖ فَإِن تَنَٰزَعۡتُمۡ فِي شَيۡءٖ فَرُدُّوهُ إِلَى ٱللَّهِ وَٱلرَّسُولِ إِن كُنتُمۡ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ وَأَحۡسَنُ تَأۡوِيلًا ٥٩

58. Lalle Allah Yana umartar ku da ku mayar da amanoni ga masu su, kuma idan za ku yi hukunci a tsakanin mutane, to ku yi hukunci da adalci. Lalle kam madalla da abin da Allah Yake muku wa’azi da shi. Lalle Allah Ya kasance Mai ji ne, Mai gani.

59. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi ɗa’a ga Allah, kuma ku yi ɗa’a ga Manzo da kuma majiɓinta lamarinku. Idan kun yi jayayya a kan wani abu, to ku mayar da shi zuwa ga Allah da Manzonsa in kun kasance kun yi imani da Allah da ranar ƙarshe. Wannan shi ne mafi alheri, kuma mafi kyan makoma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar bayinsa muminai da su mayar da amana ga masu ita, kuma idan za su yi hukunci tsakanin mutane, to su yi musu adalci. Madalla da wannan umarni da Allah yake yi na mayar da amana ga masu ita da hukunci na adalci tsakanin mutane. Lalle Allah mai jin maganganun kowa ne, mai ganin duk ayyukansu, don haka zai yi musu sakayya a kansu. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ci gaba da umartar muminai, da su yi masa ɗa’a, kuma su yi wa Manzonsa (ﷺ) ɗa’a, ta hanyar aiki da umarninsu da barin abin da suka hana. Hakanan su yi ɗa’a ga shugabanninsu na addini, watau malamai da shugabanni masu mulki, amma ɗa’ar da bata saɓa wa Allah da Manzonsa (ﷺ) ba. Duk sanda suka yi umarni da abin da ya saɓa wa Allah da Manzonsa, to ba za a yi musu ɗa’a a kai ba.

An karɓo daga Ali ɗan Abu Ɗalib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Annabi (ﷺ) ya aiki wata runduna, ya shugabantar musu da wani mutumin Madina, ya umarce su da su yi masa biyayya. Sai wani lokaci suka ɓata masa rai, ya yi fushi, sai ya ce: Ba Annabi (ﷺ) ya umarce ku da ku yi mini ɗa’a ba?” Suka ce: “An yi haka.” Sai ya ce: “Ku tara mini ƙirare.” Sai suka tara masa. Sai ya ce: “Ku hura mini wuta.” Sai suka hura. Sai ya ce: “To ku faɗa cikinta.” Sai wasu suka yunƙura za su faɗa, sai wasu suka riƙe su, suna ce musu: “Saboda tsoron shiga wuta ne ya sa muka gudu zuwa ga Annabi (ﷺ).” Haka suka yi ta jayayya har wutar ta mutu, shi kuma Shugaban nasu ya huce. Sai labari ya je wa Annabi (ﷺ), sai ya ce: “Da sun kuskura sun shiga cikinta, to da ba za su fito ba har zuwa tashin alƙiyama. Ana yin ɗa’a ne ga abin da ya dace da shari’a.” [Bukhari #4340, da Muslim #1840].

Har wa yau dai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da cewa, idan sun yi saɓani a tsakaninsu, to su nemi warware wannan saɓani ta hanyar komawa ga littafin Allah, Alƙur’ani, da kuma sunnar Manzon Allah (ﷺ) idan har sun yi imani da Allah da ranar lahira. Yin haka shi ne mafi alheri gare su a addininsu da duniyarsu da lahirarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yarda da wani hukuncin da ya saɓa wa na Allah da Manzonsa da fifita shi a kan hukuncinsu ko daidaita shi da nasu, kafirci ne.

2. Imanin mutum ba zai inganta ba sai ya kafirce wa duk wani abu da ake bauta wa ba Allah ba.

3. Wajabcin watsi da duk wani wanda magana da shi ba ta da amfani.

4. Mai aikata saɓon Allah, ko da an bijire masa, wannan ba zai hana a ci gaba da yi masa nasiha a ɓoye ba; a yi masa gamsasshen wa'azi idan ana sa ran zai gyaru.

5. Ɗa'a ga Manzon Allah (ﷺ) wajibi ce a kan duk wani mumini.

6. Manzannin Allah ma'asumai ne gaba ɗayansu, shi ya sa aka yi umarni da a yi musu ɗa'a sake ba ƙaidi.

7. Zuwa ga Annabi (ﷺ) don neman gafarar Allah idan an yi wani laifi ya taƙaita ne a lokacin rayuwarsa, shi ya sa aka ce: "ya nema musu gafarar Allah". [Duba, Bashir As-Sahsawani, *Siyanatul Insan*, Shafi na 6-26].

8. Wajibi ne a kan Musulmi idan an faɗa masa hukuncin da Manzon Allah (ﷺ) ya zartar, kada ya ji wani ƙunci a zuciyarsa.

9. Wanda zai yarda da hukuncin Manzon Allah (ﷺ) dole ne ya yarda a zuciyarsa da kuma a zahirinsa. Wannan shi ne ma'anar kore ƙuncin zuciya da kuma sallamawa ta zahiri.

Suratun Nisa'i (60-65)

أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ يَزۡعُمُونَ أَنَّهُمۡ ءَامَنُواْ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبۡلِكَ يُرِيدُونَ أَن يَتَحَاكَمُوٓاْ إِلَى ٱلطَّٰغُوتِ وَقَدۡ أُمِرُوٓاْ أَن يَكۡفُرُواْ بِهِۦ وَيُرِيدُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَن يُضِلَّهُمۡ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ٦٠ وَإِذَا قِيلَ لَهُمۡ تَعَالَوۡاْ إِلَىٰ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ وَإِلَى ٱلرَّسُولِ رَأَيۡتَ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ يَصُدُّونَ عَنكَ صُدُودٗا ٦١ فَكَيۡفَ إِذَآ أَصَٰبَتۡهُم مُّصِيبَةُۢ بِمَا قَدَّمَتۡ أَيۡدِيهِمۡ ثُمَّ جَآءُوكَ يَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ إِنۡ أَرَدۡنَآ إِلَّآ إِحۡسَٰنٗا وَتَوۡفِيقًا ٦٢ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ يَعۡلَمُ ٱللَّهُ مَا فِي قُلُوبِهِمۡ فَأَعۡرِضۡ عَنۡهُمۡ وَعِظۡهُمۡ وَقُل لَّهُمۡ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ قَوۡلَۢا بَلِيغٗا ٦٣ وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن رَّسُولٍ إِلَّا لِيُطَاعَ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ وَلَوۡ أَنَّهُمۡ إِذ ظَّلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ جَآءُوكَ فَٱسۡتَغۡفَرُواْ ٱللَّهَ وَٱسۡتَغۡفَرَ لَهُمُ ٱلرَّسُولُ لَوَجَدُواْ ٱللَّهَ تَوَّابٗا رَّحِيمٗا ٦٤ فَلَا وَرَبِّكَ لَا يُؤۡمِنُونَ حَتَّىٰ يُحَكِّمُوكَ فِيمَا شَجَرَ بَيۡنَهُمۡ ثُمَّ لَا يَجِدُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ حَرَجٗا مِّمَّا قَضَيۡتَ وَيُسَلِّمُواْ تَسۡلِيمٗا ٦٥

60. Shin ba ka ganin waɗannan da suke riya cewa sun yi imani da abin da aka saukar maka, da abin da aka saukar gabaninka, suna nufin su kai hukunci gaban Ɗagutu (wanin Allah), alhalin an umarce su da su kafirce masa, Shaiɗan kuma yana nufin ya ɓatar da su ɓata mai nisa?

61. Kuma idan an ce da su: "Ku zo ga abin da Allah Ya saukar, kuma ku zo ga wannan Manzo," sai kawai ka ga munafuƙai suna bijire maka matuƙar bijirewa.62. To yaya halinsu zai kasance idan wata musiba ta sauka a kansu saboda abin da hannayensu suka gabatar, sannan sai su zo maka suna rantsuwa da Allah, (suna cewa): "Ba ma nufin wani abu sai kyautatawa da kuma haɗin kai."?

63. Waɗannan su ne waɗanda Allah Yake sane da abin da ke cikin zukatansu, don haka ka kawar da kai daga kansu kuma ka yi musu wa'azi kuma ka faɗa musu magana a karan-kawunansu magana mai shiga zukata.

64. Kuma ba Mu taɓa aiko wani manzo ba, face sai don a yi masa ɗa'a da izinin Allah. Kuma da a ce lokacin da suka zalunci kawunansu sun zo maka, sun nemi Allah Ya gafarta musu, sannan Manzo ya roƙa musu gafara, to tabbas da sun sami Allah Yana Mai yawan karɓar tuba, Mai jin ƙai.

65. To ina rantsuwa da Ubangijinka, ba za su yi imani ba har sai sun kai hukunci a gabanka game da duk abin da ya faru na saɓani a tsakaninsu, sannan ba su ji wani ƙunci a cikin zukatansu ba game da abin da ka zartar na hukunci, kuma su miƙa wuya miƙawa gaba ɗaya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa Annabinsa (ﷺ) ishara da cewa, shin bai yi mamakin halin waɗanda suke ƙaryar sun yi imani da Alƙur'ani da littattafan da aka saukar a baya ba, amma duk da haka suna kai hukuncinsu ga wani abin da ya saɓa wa abin da Allah ya saukar, alhalin an umarce su da su kafirce masa, kuma Shaiɗan yana neman ya ɓatar da su su yi nesa da hanyar gaskiya? Duk sa'adda za a kirawo su don a yi musu hukunci da abin da Allah ya saukar a Alƙur'ani da sunnar Annabi (ﷺ), sai munafuƙan su riƙa bijire wa wannan kiran, suna kuma hana mutane sauraren sa.
To yaya halinsu zai kasance yayin da wata musiba ta auko musu saboda kafircinsu da zunubbansu, sannan suka garzayo wajen shi Ma'aiki (ﷺ) suna ba da uzuri, tare da rantsuwar ƙarya cewa su fa ba su kai hukuncinsu ga masu hukuncin da ya saɓa wa na Allah ba, sai don su ga sun kyautata musu, kuma an sami fahimtar juna a tsakani, amma su ba su yarda da cewa wannan hukuncin gaskiya ne ba?

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Akwai wani boka sunanshi Abu Burdatul Aslami, Yahudawa suna kai ƙara wajensa ya yi musu hukunci. Sai wasu Musulmi daga ƙabilar Aslam suka yi rigima a tsakaninsu, sai suka kai ƙara wajensa. Sai wannan ayar ta sauka. [Ibn Abi Hatim, *Tafsir* #5547 da Ibn Jarir At-Tabari 8:510 (Shakir)].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya san abin da yake cikin zukatansu na munafunci da mummunar manufa, kuma zai yi musu sakayya a kai, kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi watsi da su, kuma ya yi musu wa'azi, ya faɗa musu magana mai ratsa jiki, mai shiga zukata.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimar aiko da annabawa zuwa mutanensu da cewa; ya aiko su ne don a yi musu ɗa'a, a aikata abin da suka yi umarni da shi, a bar abin da suka hana. Kuma Allah ya yi haka ne da izininsa da kuma ganin damarsa.
Waɗannan munafuƙai masu kai ƙara wajen wasu masu saɓa wa Allah da Manzonsa, Allah ya faɗa musu cewa, da a ce lokacin da za su faɗa cikin wancan zunubi na kai ƙara ga wanin Allah da Manzonsa (ﷺ), da sun zo wajen Manzon Allah (ﷺ) sun faɗa masa laifin da suka aikata, sannan suka nemi gafarar Allah, suka tuba, kuma Manzon Allah (ﷺ) shi ma ya nema musu gafara a wurin Allah, da sun yi haka, da sun sami yafiya daga Allah da karɓar tubansu da yi musu rahama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi rantsuwa da kansa cewa, Na rantse da Ubangijinka, ya kai wannan Annabi, babu wanda zai yi imani karɓaɓɓe, har sai sun sa ka mai yanke hukunci a tsakaninsu game da duk wani abu da zai faru a tsakaninsu na husuma, sannan idan ka yanke hukunci a tsakaninsu, kada su ji wani ƙunci ko takuruwa a zukatansu game da hukuncin da ka yanke, su kuma miƙa wuya su sallama gaba ɗaya.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Zubairu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wani mutumin Madina rigima ta haɗa shi da Zubairu ɗan Awwam (Allah ya ƙara masa yarda) game da wata magudanar ruwa wadda suke shayar da dabinonsu daga gare ta. Sai mutumin nan na Madina ya ce wa Zubair: "Ka sako wannan ruwan ya ci gaba da wucewa." Sai Zubairu ya ƙi yarda ya saki. Sai suka kai ƙara gaban Manzon Allah (ﷺ). Sai Manzon Allah (ﷺ) ya yanke hukunci da ce wa Zubairu: "Ka shayar da dabinonka, sannan ka saki ruwan zuwa gonar maƙocinka." Sai wannan mutumin Madinan ya ji haushin wannan hukunci, ya ce: "Don yana ɗan goggonka ko?" Sai fuskar Annabi (ﷺ) ta canza, sai ya ce: "Ya Zubairu, shayar da gonarka, sannan ka toshe ruwan har sai ya koma tushen shingen gonarka." Zubairu ya ce: "Ina tsammanin wannan ayar a kan haka ta sauka." [Bukhari #2359, da Muslim #2357].

Wannan maganar ta ƙarshe ba ta nuna a dalilin wannan ƙissa ne ayar ta sauka, sai dai ayar ta shafi irin wannan abu da ya faru a wannan ƙissa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin raunin ɗan'adam da cewa, ba zai iya aikata duk abin da aka umarce shi ba, musamman idan akwai raunin imani.

2. Yi wa Allah ɗa'a da bin umarninsa shi ne hanyar dacewa da kowane alheri.

3. Gwargwadon aikin mutum shi ne gwargwadon sakamakonsa. Idan mutum ya yi aiki mai kyau karɓaɓɓe a wajen Allah, to wannan aiki nasa zai haifar masa da wani aikin mai kyau a matsayin sakamako gare shi.

4. Nuna wa ɗan'adam ya nemi falala a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) domin tasa ce, shi ne mai ba da ita ga wanda ya ga dama.

5. Fitar da mutane daga gidajensu abu ne mai ciwon gaske, dubi yadda Allah a nan ya haɗa shi da kashe kai.

6. Ɓacin maganar masu cewa, mutum ya bauta wa Allah ba don tsoron wutarsa ba, ba kuma don kwaɗayin Aljannarsa ba. Idan haka gaskiya ne, to da faɗar za a ba da lada mai yawa ya zama ba shi da wani amfani a ayar. Domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai kawo ambaton 'lada' ba, ya kuma kwaɗaitar a kan a yi aiki a same shi, sai domin kasancewarsa ba zai raunana niyya ba, kuma bai saba wa ikhlasi ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta Annabinsa (ﷺ) da sahabbansa da cewa, suna ibada, suna neman wata falala daga Allah. [Dubi, *Suratul Fathi*, aya ta 29].

7. Annabawa su ne gaba da waliyyai a daraja a wurin Allah, shi ya sa Allah ya fara da ambaton su a wannan wuri.

Suratun Nisa'i (66-70)

وَلَوْ أَنَّا كَتَبْنَا عَلَيْهِمْ أَنِ ٱقْتُلُوٓاْ أَنفُسَكُمْ أَوِ ٱخْرُجُواْ مِن دِيَٰرِكُم مَّا فَعَلُوهُ إِلَّا قَلِيلٌ مِّنْهُمْۖ وَلَوْ أَنَّهُمْ فَعَلُواْ مَا يُوعَظُونَ بِهِۦ لَكَانَ خَيْرًا لَّهُمْ وَأَشَدَّ تَثْبِيتًا ﴿٦٦﴾ وَإِذًا لَّأٰتَيْنَٰهُم مِّن لَّدُنَّآ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿٦٧﴾ وَلَهَدَيْنَٰهُمْ صِرَٰطًا مُّسْتَقِيمًا ﴿٦٨﴾ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنْعَمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّٰلِحِينَۚ وَحَسُنَ أُوْلَٰٓئِكَ رَفِيقًا ﴿٦٩﴾ ذَٰلِكَ ٱلْفَضْلُ مِنَ ٱللَّهِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ عَلِيمًا ﴿٧٠﴾

66. Kuma in da a ce lalle Mun wajabta musu cewa: "Ku kashe kawunanku ko ku fita daga gidajenku," da 'yan kaɗan ne daga cikinsu za su aikata hakan. Da a ce sun aikata abin da ake musu wa'azi da shi, to da ya fi alheri, kuma da ya fi tsananin tabbatar da su (a kan hanya madaidaiciya).

67. Da sun yi hakan kuwa tabbas da Mun ba su wani babban lada daga wajenmu.

68. Kuma tabbas da Mun shiryar da su tafarki madaidaici.

69. Kuma duk wadanda suka yi wa Allah ɗa'a da wannan Manzon, to waɗannan suna tare da waɗanda Allah Ya yi musu ni'ima, su ne annabawa da siddiƙai da shahidai da salihan bayi. Kuma madalla da waɗannan abokai.

70. Wannan falala ce daga Allah. Kuma Allah Ya isa masanin (dukkan lamura).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin cewa, waɗannan mutane masu kai ƙara gaban waɗanda za su yi musu hukuncin da ba na Allah ba, da za a ce musu su kashe kansu, ko sashinsu ya kashe wani sashi, ko kuma su fita su bar gidajensu, to 'yan kaɗan ne daga cikinsu za su aikata hakan. Da a ce za su yi aiki da wa'azin da ake yi musu kullum, su bi umarnin Allah da Manzonsa (ﷺ), su bar abin da suka hana su, to da shi ya fi zama alheri a gare su, kuma ya fi tabbatar da su kan tafarki na gaskiya, da kuma Allah ya ba su lada mai girma, kamar yadda ya alƙarwanta musu, kuma ya shiryar da su zuwa ga tafarki madaidaici.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya bi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya bi Manzonsa (ﷺ), to zai sami shiga Aljanna, kuma zai kasance tare da ƙungiyar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu ni'imar shiriya zuwa ga hanya madaidaiciya, watau annabawa da siddiƙai, waɗanda suka sami kamala wajen gaskata Allah da Manzonsa da aiki da gaskiya, da kuma shahidai waɗanda aka kashe su a wajen ɗaukaka addinin Allah, da salihai waɗanda suka gyara cikinsu da wajensu. Madalla da irin wannan ƙungiya ta arziki.

An karɓo daga A'isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: Wani mutum ya zo wurin Annabi (ﷺ) ya ce: "Ya Manzon Allah (ﷺ), na fi son ka fiye da kaina, kuma na fi son ka fiye da iyayena. Nakan kasance a gida a zaune, amma da zarar na tuna ka sai in kasa daurewa sai na zo na gan ka. To duk lokacin da na tuno mutuwata da mutuwarka, sai in fahimci cewa, idan ka shiga Aljanna, to za a ɗaga matsayinka tare da annabawa; ni kuma idan na shiga Aljanna, to ina tsoron ba zan ƙara ganin ka ba." Annabi (ﷺ) ya yi shiru bai ba shi amsa ba, har sai da Mala'ika Jibrilu ya saukar da wannan ayar." [At-Tabarani, *Al-Mu'ujam Al-Ausat* #477].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, wannan sakamako da ya yi wa masu biyayya ga Allah da Annabinsa, wata falala ce daga gare shi da yake ba da ita ga duk wanda ya cancanta ya ba shi. Allah kuma ya isa mai cikakken ilimi game da ayyukan bayinsa, kuma shi ya fi sanin wanda ya fi cancantar shiriya, ya shiryar da shi zuwa ga madaidaicin tafarki.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne mumini ya zama ko da yaushe yana farke idonsa biyu.

2. Nuna kasala wajen aikin alheri da ja da baya yana daga cikin abubuwan da suke kai mutum ga munafunci da ɓata.

3. Tsare wasu muminai masu rauni a hannun kafirai, suna zaluntar su, suna gallaza musu, yana daga cikin dalilai da za su sanya muminai su fita yaƙi saboda Allah.

4. Bambancin mayaƙi mumini da wanda yake kafiri. Shi mumini yana yaƙinsa domin Allah da neman yardarsa, ta hanyar bin umarninsa; shi kuma kafiri yana yaƙi ne don biyayya ga tafarkin Shaiɗan da zaluntar bayin Allah.

Suratun Nisa'i (71-76)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ خُذُواْ حِذۡرَكُمۡ فَٱنفِرُواْ ثُبَاتٍ أَوِ ٱنفِرُواْ جَمِيعٗا ٧١ وَإِنَّ مِنكُمۡ لَمَن لَّيُبَطِّئَنَّ فَإِنۡ أَصَٰبَتۡكُم مُّصِيبَةٞ قَالَ قَدۡ أَنۡعَمَ ٱللَّهُ
عَلَيَّ إِذۡ لَمۡ أَكُن مَّعَهُمۡ شَهِيدٗا ٧٢ وَلَئِنۡ أَصَٰبَكُمۡ فَضۡلٞ مِّنَ ٱللَّهِ لَيَقُولَنَّ كَأَن لَّمۡ تَكُۢنۢ بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَهُۥ مَوَدَّةٞ يَٰلَيۡتَنِي كُنتُ مَعَهُمۡ فَأَفُوزَ

فَوۡزًا عَظِيمَا ٧٣ ۞فَلۡيُقَٰتِلۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ ٱلَّذِينَ يَشۡرُونَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا بِٱلۡأٓخِرَةِۚ وَمَن يُقَٰتِلۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَيُقۡتَلۡ أَوۡ يَغۡلِبۡ فَسَوۡفَ نُؤۡتِيهِ أَجۡرًا عَظِيمَا ٧٤ وَمَا لَكُمۡ لَا تُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلۡمُسۡتَضۡعَفِينَ مِنَ ٱلرِّجَالِ وَٱلنِّسَآءِ وَٱلۡوِلۡدَٰنِ ٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَآ أَخۡرِجۡنَا مِنۡ هَٰذِهِ ٱلۡقَرۡيَةِ ٱلظَّالِمِ أَهۡلُهَا وَٱجۡعَل لَّنَا مِن لَّدُنكَ وَلِيّٗا وَٱجۡعَل لَّنَا مِن لَّدُنكَ نَصِيرًا ٧٥ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ ٱلطَّٰغُوتِ فَقَٰتِلُوٓاْ أَوۡلِيَآءَ ٱلشَّيۡطَٰنِۖ إِنَّ كَيۡدَ ٱلشَّيۡطَٰنِ كَانَ ضَعِيفًا ٧٦

71. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi taka-tsantsan, kuma ku fita ƙungiya-ƙungiya, ko kuma ku fita gaba ɗaya.

72. Kuma lalle a cikinku akwai wanda yake daƙilewa, idan wata musiba ta same ku, sai ya ce: “Haƙiƙa Allah Ya yi mini ni’ima da ban halarci (yaƙin) tare da su ba.”

73. Amma idan wata falala ta same ku daga Allah, tabbas zai riƙa cewa, kamar daɗai ba wata soyayya tsakaninku da shi: “Ina ma na kasance tare da su, don ni ma in rabauta rabo mai girma?”

74. To waɗanda suke sayen rayuwar lahira da ta duniya, sai su yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah. Duk wanda yake yin yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah kuwa, sai aka kashe shi ko kuma ya yi galaba, to za Mu ba shi lada mai girma.

75. Kuma me ya same ku ne, da ba za ku yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah ba, da kuma kuɓutar da raunana maza da mata da yara ƙanana, waɗanda suke cewa: “Ya Ubangijinmu, Ka fitar da mu daga wannan alƙaryar wadda mutanenta suke azzalumai, kuma Ka sanya mana wani majiɓincin lamari daga wurinka, kuma Ka sanya mana wani mai taimako daga wurinka?”

76. Waɗanda suka yi imani suna yaƙi ne don ɗaukaka kalmar Allah; waɗanda kuma suka kafirce suna yin yaƙi ne don kare Ɗagutu; to ku yaƙi masoya Shaiɗan; lalle makircin Shaiɗan rarrauna ne.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai ne da su yi taka-tsantsan game da maƙiyansu, ta hanyar zama cikin shiri ko da yaushe. Idan kuma sun zo fita yaƙi, to su fita ƙungiya-ƙungiya, ko kuma su fita gaba ɗaya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗakar da muminai cewa, a cikinsu fa akwai munafuƙai waɗanda ba sa son fita jihadi tare da Manzon Allah (ﷺ), suna kuma hana wasu fita. Duk lokacin da wata masifa ta auka wa muminai waɗanda suka fita jihadi, aka kashe wasu daga cikinsu, ko aka raunana wasu, sai ka ga ɗaya daga cikin munafuƙan nan yana cewa: “Ni dai Allah ya yi mini gyaɗar dogo da ban fita tare da su ba, da yanzu abin da ya same su ni ma ya same ni.” Amma idan Musulmi ne suka ci nasara, suka samo ganima, sai ya dawo yana magana kamar shi ba ɗan’uwa ba ne, kamar babu wani abu na soyayya a tsakaninsa da muminai, yana kuma cewa: “Ina ma na bi su a wannan karon da yanzu da ni za a raba wannan ganimar, ni ma in more sosai.”
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fuskantar da umarni na yin yaƙi don ɗaukaka kalmarsa ga duk masu kwaɗayin samun lada daga Ubangijinsu, waɗanda suka sayi lahira da duniyarsu. Kuma ya yi alƙawarin ba da gagarumin lada ga duk wanda ya yi yaƙi saboda shi, ko maƙiya sun kashe shi a fagen yaƙi, ko ba su kashe shi ba, shi kam ya yi nasara a kansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar da muminai da cewa, me zai hana su yin yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah da kuɓutar da raunana daga cikin maza da mata da yara, waɗanda koyaushe suke roƙon Ubangijinsu da ya fitar da su daga garin Makka, wanda mushirikan cikinta ba bin da suke yi sai

zalunci. Addu’arsu ita ce Allah ya samar musu da wanda zai jiɓinci lamarinsu ya taimake su ya ceto su daga hannun waɗannan azzalumai.

An karɓo daga Ubaidullahi ɗan Abdullahi ɗan Utba ya ce: Na ji Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) yana cewa: “Ni da mahaifiyata muna cikin waɗannan raunana, ni ina cikin yaran, mahaifiyata kuma tana cikin manyan mata.” [Bukhari #1357].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bambance tsakanin muminai masu yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah da ceto raunana daga zaluncin azzalumai, da kuma waɗanda suke yaƙi don biyayya ga wani abin bauta ba Allah ba. Sannan Allah ya yi umarni da a yaƙi duk wanda ya rungumi Shaiɗan, yana yi masa biyayya, Allah ya tabbatar da cewa, makircin Shaiɗan rarrauna ne ainun, don haka kada ya ba su tsoro.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutum zai iya zaton duk abin da aka umarce shi da shi zai iya aikata shi, to amma yayin da umarnin ya tabbata, sai ya juya baya, ya noƙe. Shi ya sa Annabi (ﷺ) yake cewa: “Kada ku riƙa fatan karawa da maƙiya; ku dai ku roƙi Allah zaman lafiya, to amma idan har kun haɗu da su a filin daga, to sai ku jure, domin Aljanna tana ƙarƙashin inuwar takubba.” [Bukhari #3024, da Muslim #1742].Don haka bai kamaci mutum tun farko ya shiga aikin da ya san ba zai iya ba, domin idan har ya fara sannan daga baya ya watsar, to ƙimarsa a idanun mutane za ta zube, su riƙa cewa: “Da man wane ya fiye garaje.”

2. Idan mutum ba zai iya yin jihadi ba, to ya kyautata ayyukan ibadarsa, kamar salla da azumi da zakka da sauransu.

3. Wajibi ne mutum ya shirya wa zuwan mutuwarsa, domin za ta riske shi ne babu makawa.

4. Wajibi ne a kan mutum idan ya sami wata ni’ima, to ya gode wa Allah, saboda wannan falala ce daga Allah, ba don ya zama dole Allah ya ba shi ita ba. Idan kuma wata musifa ce ta same shi, to ya binciki kansa, ya yi wa kansa hisabi, ya tuba daga abin da yake yi na saɓa wa Allah, sai Allah ya yaye masa ita.

5. Rushe camfi gaba ɗaya. Domin camfi shirka ne, kuma aiki ne irin na kafiran farko.

Suratun Nisa’i (77-79)

أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ قِيلَ لَهُمۡ كُفُّوٓاْ أَيۡدِيَكُمۡ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ فَلَمَّا كُتِبَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقِتَالُ إِذَا فَرِيقٞ مِّنۡهُمۡ يَخۡشَوۡنَ ٱلنَّاسَ كَخَشۡيَةِ ٱللَّهِ أَوۡ أَشَدَّ خَشۡيَةٗۚ وَقَالُواْ رَبَّنَا لِمَ كَتَبۡتَ عَلَيۡنَا ٱلۡقِتَالَ لَوۡلَآ أَخَّرۡتَنَآ إِلَىٰٓ أَجَلٖ قَرِيبٖۗ قُلۡ مَتَٰعُ ٱلدُّنۡيَا قَلِيلٞ وَٱلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ لِّمَنِ ٱتَّقَىٰ وَلَا تُظۡلَمُونَ فَتِيلًا ٧٧ أَيۡنَمَا تَكُونُواْ يُدۡرِككُّمُ ٱلۡمَوۡتُ وَلَوۡ كُنتُمۡ فِي بُرُوجٖ مُّشَيَّدَةٖۗ وَإِن تُصِبۡهُمۡ حَسَنَةٞ يَقُولُواْ هَٰذِهِۦ مِنۡ عِندِ ٱللَّهِۖ وَإِن تُصِبۡهُمۡ سَيِّئَةٞ يَقُولُواْ هَٰذِهِۦ مِنۡ عِندِكَۚ قُلۡ كُلّٞ مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِۖ فَمَالِ هَٰٓؤُلَآءِ ٱلۡقَوۡمِ لَا يَكَادُونَ يَفۡقَهُونَ حَدِيثٗا ٧٨ مَّآ أَصَابَكَ مِنۡ حَسَنَةٖ فَمِنَ ٱللَّهِ وَمَآ أَصَابَكَ مِن سَيِّئَةٖ فَمِن نَّفۡسِكَۚ وَأَرۡسَلۡنَٰكَ لِلنَّاسِ رَسُولٗاۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدٗا ٧٩

77. Shin ba ka ganin waɗanda aka ce da su: “Ku kame hannayenku kuma ku tsayar da salla kuma ku bayar da zakka?” To yayin da aka wajabta musu yaƙi, sai ga wani ɓangare daga cikinsu suna jin tsoron mutane kamar yadda suke jin tsoron Allah, ko ma fiye da hakan. Kuma sai suka ce: “Ya Ubangijinmu, don me Ka wajabta mana yin yaƙi, me ya hana Ka jinkirta mana zuwa wani lokaci makusanci?” Ka ce: “Jin daɗin duniya kaɗan ne, lahira kuwa ita ce mafi alheri ga wanda ya yi taƙawa, kuma ba za a zalunce ku ba, ko da gwargwadon zaren ƙwallon dabino ne.”

78. Duk inda kuka kasance mutuwa za ta riske ku, ko da kuna cikin waɗansu ganuwoyi masu tsawo. Kuma idan wani kyakkyawan abu ya same su, sai su ce: “Wannan ai daga Allah ne.” Idan kuma wani mummunan abu ya same su, sai su ce: “Wannan daga wajenka ne.” Ka ce: “Dukkansu daga Allah ne.” Shin me ya sami waɗannan mutane ne ba sa kusa ma da su fahimci zance?

79. Duk wani kyakkyawan abu da ya same ka, to daga Allah ne; duk kuma wani mummunan abu da ya same ka, to daga wajen ka ne. Kuma Mun aiko ka Manzo ga mutane. Kuma Allah Ya isa Mai shaida (a kan haka).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayani ne game da wasu sahabbai waɗanda suka yi ta roƙon a farlanta musu jihadi, alhali ana faɗa musu cewa, su bar maganar yaƙar mushirikai, su dai su tsayar da salla, su ba da zakka, amma sai ba su daina roƙon ba. To yayin da aka farlanta musu yaƙin, sai ga wasu daga cikinsu suna tsoron mutane kamar yadda suke tsoron Allah, ko ma fiye da haka; suka riƙa cewa: Ya Ubangiji, me ya sa ka farlanta mana yaƙi a daidai wannan lokaci, me ya sa ba ka jinkirta shi zuwa wani lokaci daban ba? Sai Allah ya umarci Annabinsa da ya faɗa musu cewa: Komai na duniya wani ɗan jin daɗi ne ƙanƙani, kuma mai gushewa; abin da Allah ya tanadar wa masu taƙawaa da masu yi masa biyayya a lahira, ya fi duniya da abin da yake cikinta, kuma ba za a zalunce su da komai ba.
Sannan Allah ya nuna cewa, mutuwar da suke guje wa sai ta riske su a ko’ina za su shiga a bayan ƙasa, ko da kuma za su ɓoye ne a waɗansu ganuwoyi masu dogayen gini da tsaro mai tsanani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin masu ƙaryata Annabi (ﷺ) da cewa, duk sa’adda wani alheri ya same su sai su ce wannan daga Allah ne, wato shi ne ya ba su; idan kuma wani mummunan abu ya same su, sai su camfa Manzon Allah (ﷺ), su ce ai saboda shi ne wannan musifar ta same su. Sai Allah ya umarci Annabi (ﷺ) ya mayar musu da martani cewa, duk abin da ya auku gare su, mai daɗi da maras daɗi, duk daga Allah ne, shi ne ya hukunta faruwarsa ba wani ba, to amma me ya sa masu irin waɗannan maganganu ba sa fahimtar duk wata Magana da ake faɗa musu?
A ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa ɗan'adam cewa, duk abin da ya same shi na farin ciki, kamar haihuwa da dukiya da mulki da sauransu, to ya sani daga Allah ne, falalarsa ce da rahamarsa a gare shi; abin da kuma ya same shi marar daɗi a rayuwarsa, to wannan shi ya jawo wa kansa ta hanyar zunubinsa. Allah kuma ya gaya wa Annabi Muhammadu (ﷺ), cewa shi ne ya aiko shi Manzo ga mutane gaba ɗaya, don ya isar musu da shari’arsa, kuma Allah ya isa ya zama shaida a kan cewa ya isar da wannan saƙo, bai ɓoye komai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Miƙa wuya ga Annabi (ﷺ) da yi masa ɗa’a, miƙa wuya ne ga Allah; bin umarninsa shi ma bin umarnin Allah ne, saɓa masa kuma saɓa wa Allah ne. Don haka da Alƙur’ani da sunnar Annabi (ﷺ) duk abu ɗaya ne a wajen bayanin manufofin Musulunci.

2. Gargaɗi a kan munafunci, wato mutum ya zama mai fuska biyu; idan yana tare da muminai ya nuna musu ƙauna da soyyaya; idan ya bar su, ya koma gefe guda, ya nuna wata fuskar daban. Dole ne mutum ya zama mai magana ɗaya da zuciya ɗaya.

3. Wanda aka fitar da ran gyaruwarsa, ya halatta a fita sha’aninsa, kada koyaushe a damu da lamarinsa, ko da kuwa a wani lokaci za a sake waiwayar sa da wa’azi da nasiha.

4. Kwaɗaitarwa a kan tuntuntuni a tsanake game da Alƙur’ani da ƙoƙarin fahimtar ma’anoninsa, domin fitar da ɗimbin hikimomi da ma’anonin da ya ƙunsa.

5. Duk wata magana ko wani littafi wanda ba wahayi ba, to ana iya samun saɓani a cikinsa, ana iya ganin tufka da warwara, ana iya samun kurakurai a cikinsa.

6. Gargaɗi da jan kunne ga masu gaggawar baza kowanne irin labari suka ji, ba tare da sun tabbatar da gaskiyarsa ba da kuma masalahar baza shi.

7. Al'amuran da suka shafi makomar al'umma da siyasar gudanar da al'umma, bai kamata kowa da kowa ya yi ruwa da tsaki a cikinsu ba; wajibi ne a bar su a hannun masana, waɗanda suka goge a al'amuran rayuwa, su tattauna, su fitar da matsaya guda.

8. Wajibi ne mutum ya fara da kansa a wajen aikata duk wani wajibi kafin ya kira wani a kansa.

9. Shiriyar wani ba a hannun kowa take ba, tana ga hannun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne.

Suratun Nisa'i (80-84)

مَّن يُطِعِ ٱلرَّسُولَ فَقَدۡ أَطَاعَ ٱللَّهَۖ وَمَن تَوَلَّىٰ فَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ عَلَيۡهِمۡ حَفِيظٗا ٨٠ وَيَقُولُونَ طَاعَةٞ فَإِذَا بَرَزُواْ مِنۡ عِندِكَ بَيَّتَ طَآئِفَةٞ مِّنۡهُمۡ غَيۡرَ ٱلَّذِي تَقُولُۖ وَٱللَّهُ يَكۡتُبُ مَا يُبَيِّتُونَۖ فَأَعۡرِضۡ عَنۡهُمۡ وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا ٨١ أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلۡقُرۡءَانَۚ وَلَوۡ كَانَ مِنۡ عِندِ غَيۡرِ ٱللَّهِ لَوَجَدُواْ فِيهِ ٱخۡتِلَٰفٗا كَثِيرٗا ٨٢ وَإِذَا جَآءَهُمۡ أَمۡرٞ مِّنَ ٱلۡأَمۡنِ أَوِ ٱلۡخَوۡفِ أَذَاعُواْ بِهِۦۖ وَلَوۡ رَدُّوهُ إِلَى ٱلرَّسُولِ وَإِلَىٰٓ أُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنۡهُمۡ لَعَلِمَهُ ٱلَّذِينَ يَسۡتَنۢبِطُونَهُۥ مِنۡهُمۡۗ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ لَٱتَّبَعۡتُمُ ٱلشَّيۡطَٰنَ إِلَّا قَلِيلٗا ٨٣ فَقَٰتِلۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ لَا تُكَلَّفُ إِلَّا نَفۡسَكَۚ وَحَرِّضِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۖ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَكُفَّ بَأۡسَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۚ وَٱللَّهُ أَشَدُّ بَأۡسٗا وَأَشَدُّ تَنكِيلٗا ٨٤

80. Duk wanda ya yi wa wannan Manzo ɗa'a, to haƙiƙa ya yi wa Allah ɗa'a ne; wanda kuwa ya bijire, to ba Mu aiko ka a matsayin mai tsaron su ba.

81. Kuma sukan ce: "Ai ba mu da wani abu sai biyayya." To idan suka fita daga wajenka, sai wata ƙungiya daga cikinsu, su riƙa ƙulla wani abu daban cikin dare, saɓanin abin da suke faɗa; Allah kuwa Yana rubuta duk wani abu da suke ƙullawa da daddare; to ka kawar da kai daga kansu, kuma ka dogara ga Allah. Allah kuwa Ya isa abin dogaro.

82. Shin ba za su yi zuzzurfan tunani game da ayoyin Alƙur'ani ba ne? Kuma da a ce ya kasance daga wajen wani yake ba Allah ba, tabbas da sun sami saɓani mai yawa a cikinsa.

83. Kuma idan wani lamari ya zo musu wanda ya shafi zaman lafiya ko tsoro, sai su yaɗa shi. Da a ce sun mayar da shi zuwa ga wannan Manzo da shugabanni daga cikinsu, da lalle waɗanda suke bin ƙwaƙƙwafin al'amarin sun san (dacewar a yaɗa shi ko a'a). Kuma ba don falalar Allah da rahamarsa a gare ku ba, tabbas da kun bi Shaiɗan, in ban da 'yan kaɗan (daga cikinku).

84. To ka yi yaƙi domin ɗaukaka kalmar Allah, ba a ɗora maka nauyin tilasta kowa ba sai kanka. Kuma ka zaburar da muminai; Allah zai dankwafe ƙarfin waɗanda suka kafirta; kuma Allah Shi ne Mafi tsananin ƙarfi, kuma Mafi tsananin uƙuba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tabbatar da cewa, duk wanda ya yi wa Manzon Allah (ﷺ) ɗa'a, to Allah ya yi wa; wanda kuwa ya bijire masa, to wannan kansa ya cuta, ba za a nemi wani bayani a kansa daga wurin Annabi (ﷺ) ba, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai aiko shi don ya

zama mai tsaro a kan ayyukan bayinsa, ko mai hisabi a kansu ba. Ya dai aiko shi ne don kawai ya isar musu da saƙon Allah; idan ya isar da saƙon, to ya gama aikinsa, kuma ladansa yana wurin Allah, zai cika masa, ko sun yi masa ɗa'a ko ba su yi ba.
A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin abin da munafuƙai suke yi yayin da suka zo ga Annabi (ﷺ). Sai su riƙa nuna masa za su yi masa biyayya, kuma ba za su saɓa masa ba, to amma idan sun keɓance su-ya-su cikin dare sai su ƙulla abin da yake saɓanin maganar da suka yi wa Annabi (ﷺ). Sai Allah ya gargaɗe su, da cewa, duk abin da suke ɓoyewa suna saƙawa cikin dare, Allah ya san shi yana rubuta shi, don haka kada su zaci sun kuɓuta daga kamunsa. Ya kuma umarci Annabinsa da ya yi watsi da su, kada ya damu da su, ko ya ɓata lokacinsa a kansu; shi dai ya dogara ga Allah shi kaɗai ya ishe shi mai taimako, kuma mai jiɓintar al'amarinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga munafuƙai da sauran masu jayayya da Annabi (ﷺ), a kan Alƙur'ani da ya zo musu da shi wai ba maganar Allah ba ce, maganar wani ne can daban. Allah ya ja hankalinsu da su yi duba na tsanaki da karatu na ta-nutsu game da ma'anonin Alƙur'ani. Da a ce ba daga Allah yake ba, da sun gamu da ruɗani mai yawa a cikinsa, to amma ba su taɓa ganin wata tufka da warwara ba a cikinsa. Wannan babban dalili ne mai tabbatar da cewa, Alƙur'ani maganar Allah ne, ba ƙirƙirar sa Annabi (ﷺ) ya yi ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin wani mummunan hali na waɗannan munafuƙai, a cikin zamantakewarsu da al'umma. Watau duk lokacin da suka sami wani labari mai alaƙa da samun nasara da zaman lafiya, ko mai alaƙa da da tsoro ko yaƙi, to sai su shiga watsa shi tsakanin jama'a tun kafin ya isa ga Annabi (ﷺ) da manyan sahabbansa, waɗanda su ne ya kamata su duba labarai su tantance wanda ya kamata a saki don zai taimaka wa al'umma, da wanda bai kamata a watsa shi ba don ba zai taimaka wa al'umma ba. To amma su munafuƙai suna watsa kowanne irin labari da suka ji ne, don su kawo ruɗani da saka tsoro a zukatan muminai. Allah ya bayyana cewa, da a ce sun kai waɗannan labarun zuwa ga Annabi (ﷺ) da shugabanninsu, don su duba su tantance na gaskiya da na ƙarya, su kuma tantance wanda yaɗa shi cikin jama'a zai haifar da maslaha, da wanda babu wata maslaha a cikin yaɗa shi. Da sun yi haka, da lalle masu ilimi sun gane bakin zaren kowacce magana, sun fito da bayaninta yadda yake. Allah ya faɗa wa muminai cewa, ba don falalar Allah da ya yi musu ba, da su ma sun zama kamar munafuƙai, sun bi sahun Shaiɗan wajen yayata kowanne irin labari suka ji kafin su tantance shi, sai 'yan kaɗan daga cikinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa da ya yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah, yana mai tabbatar masa cewa, ba a ɗora masa nauyin ba in ba nasa na kansa ba. Sannan ya umarce shi da ya kwaɗaitar da muminai su fita yaƙi, ya ƙarfafa musu gwiwa a kan hakan, tare da sa ran Allah zai dankwafar da duk wani yunƙuri na kafirai, domin ƙarfin Allah ya fi na kowa, kuma shi mai yin uƙuba ne ga wanda ya saɓa masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a kan taimakon juna cikin aikin alheri da bin dokokin Allah, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake saka wa masu taimakon juna.

2. Kashedi game da taimako a kan saɓon Allah da rashin gaskiya. Duk wanda ya ba da gudummawa wajen rashin gaskiya, to yana da kamasho na zunubi a kan haka.

3. Duk wanda aka yi wa gaisuwa, to ya amsa da wadda ta fi ta ko ya amsa daidai da irinta. Wannan yana daga cikin kyakkyawar mu'amala, kuma yana ƙara danƙon soyayya tsakanin Musulmi.

4. Amsa sallama wajibi ne a kan duk wanda aka yi wa sallama.

5. Mutum ko ba Musulmi ba ne ya fara yi maka sallama, to haƙƙinsa ne a kanka ka amsa masa da irin gaisuwar da ya yi maka.

6. Ba ya halatta Musulmi ya yi maka sallama irin ta Musulunci ya ce, ‘assalamu alaikum’, kai kuma ka mayar masa da gaisuwar da ba sallama ba, kamar ka ce ‘barka kadai’.

Suratun Nisa’i (85-87)

مَّن يَشۡفَعۡ شَفَٰعَةً حَسَنَةً يَكُن لَّهُۥ نَصِيبٞ مِّنۡهَاۖ وَمَن يَشۡفَعۡ شَفَٰعَةً سَيِّئَةً يَكُن لَّهُۥ كِفۡلٞ مِّنۡهَاۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ مُّقِيتًا ٨٥ وَإِذَا حُيِّيتُم بِتَحِيَّةٖ فَحَيُّواْ بِأَحۡسَنَ مِنۡهَآ أَوۡ رُدُّوهَآۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٍ حَسِيبًا ٨٦ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ لَيَجۡمَعَنَّكُمۡ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ لَا رَيۡبَ فِيهِۗ وَمَنۡ أَصۡدَقُ مِنَ ٱللَّهِ حَدِيثٗا ٨٧

85. Duk wanda ya yi (ma wani) kyakkyawar alfarma, zai samu rabonsa na lada daga gare ta; kuma duk wanda ya yi wa wani mummunar alfarma, zai samu rabonsa na zunubi daga gare ta. Kuma Allah Ya kasance Mai kiyaye komai ne.

86. Kuma idan an gaishe ku da wata gaisuwa, to ku amsa da gaisuwar da ta fi wadda aka yi muku kyau, ko ku mayar da irinta. Lalle Allah Ya kasance Mai hisabi ne a kan kowane abu.

87. Allah, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Lalle zai tattara ku a ranar alƙiyama, wadda babu kokwanto a cikinsa. Kuma wane ne ya fi Allah gaskiyar zance?

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, wanda duk ya taimaki wani a kan wani kyakkyawan al’amari, to yana da lada a kansa. Hakanan wanda ya yi ƙoƙari wajen taimakon wani a kan abin da bai dace ba, to shi ma yana da nasa kamashon na zunubi. Allah mai iko ne, mai kiyayewa, kuma mai sakayya ne a kan komai; shi zai yi wa kowa hisabi bisa ga aikinsa kyakkyawa ko mummuna.

An karɓo daga Abu Musa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance idan wani mai roƙo ya zo, ko aka nemi wata buƙata a wurinsa, sai ya ce: “Ku nema wa wasu alfarma, za a ba ku lada, kuma Allah yana zartar da abin da ya ga dama a bisa harshen Annabinsa.” [Bukhari #1432].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ladabi na gaisuwa, inda ya ce, idan aka gaishe ku da wata gaisuwa, to ku mayar da wadda ta fi ta, ko kuma ku amsa da irinta. Lalle Allah yana tattara ayyukan bayinsa, kuma shi mai yi musu hisabi ne a kansu.
An karɓo daga Imrana ɗan Husain (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya zo ga Annabi (ﷺ) ya ce: *“Assalamu alaikum*.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya amsa masa, sannan ya zauna. Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Yana da lada goma.” Sannan wani ya zo ya ce: *“Assalamu alaikum wa rahamatullah*i.” Shi ma Annabi ya amsa masa, sannan ya zauna. Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Yana da lada ashirin.” Sannan wani ma ya zo ya ce: *“Assalamu alaikum wa rahmatullahi wa barakatuhu*.” Shi ma Manzon Allah (ﷺ) ya amsa masa, sannan ya zauna. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Yana da lada talatin.” [Abu Dawud #5195, da Tirmizi #2689].
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, shi ne kaɗai abin bauta, babu wani abin da ya cancanta a bauta masa da gaskiya sai shi kaɗai, kuma zai tattara ɗaukacin halittu gaba ɗaya ranar alƙiyama domin yi musu hisabi. Wannan rana babu makawa sai ta zo, domin Allah shi ne ya faɗa, kuma babu wanda ya kai Allah faɗar magana ta gaskiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Munanan ayyuka suna haifar da wasu munanan ayyuka irinsu.

2. Shiryarwa da ɓatarwa a hannun Allah suke.

3. Kafirai suna matuƙar ƙaunar su ga sun ɓatar da Musulmi, sun mayar da su cikin kafirci irin nasu. Don haka za su yi amfani da kowace irin dama don cim ma wannan mummunar manufa tasu, ko dai ta hanyar siyasa ko tattalin arziki ko yaɗa miyagun ɗabi'u da al'adu cikin Musulmi.

4. Duk wasu masu miyagun ayyuka sukan so su sami waɗanda za su riƙa yin aiki irin nasu, domin su ƙara samun abokan tafiya.

5. Haramta ƙulla soyayya tsakanin muminai da kafirai.

6. An saka tubalin gina al'ummar Musulmi ne a kan harsashi na imani da son Allah da Manzonsa, ba a kan wani jinsi ko yare ko ƙabila ko ƙasa ba.

7. Musulunci yana fifita zaman lafiya a tsakanin al'umma, matuƙar an ba Musulmi 'yancin gudanar da addininsu kamar yadda Allah ya umarce su.

Suratun Nisa'i (88-91)

۞فَمَا لَكُمۡ فِي ٱلۡمُنَٰفِقِينَ فِئَتَيۡنِ وَٱللَّهُ أَرۡكَسَهُم بِمَا كَسَبُواْۚ أَتُرِيدُونَ أَن تَهۡدُواْ مَنۡ أَضَلَّ ٱللَّهُۖ وَمَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ سَبِيلٗا ٨٨ وَدُّواْ لَوۡ تَكۡفُرُونَ كَمَا كَفَرُواْ فَتَكُونُونَ سَوَآءٗۖ فَلَا تَتَّخِذُواْ مِنۡهُمۡ أَوۡلِيَآءَ حَتَّىٰ يُهَاجِرُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَخُذُوهُمۡ وَٱقۡتُلُوهُمۡ حَيۡثُ وَجَدتُّمُوهُمۡۖ وَلَا تَتَّخِذُواْ مِنۡهُمۡ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرًا ٨٩ إِلَّا ٱلَّذِينَ يَصِلُونَ إِلَىٰ قَوۡمِۭ بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَهُم مِّيثَٰقٌ أَوۡ جَآءُوكُمۡ حَصِرَتۡ صُدُورُهُمۡ أَن يُقَٰتِلُوكُمۡ أَوۡ يُقَٰتِلُواْ قَوۡمَهُمۡۚ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَسَلَّطَهُمۡ عَلَيۡكُمۡ فَلَقَٰتَلُوكُمۡۚ فَإِنِ ٱعۡتَزَلُوكُمۡ فَلَمۡ يُقَٰتِلُوكُمۡ وَأَلۡقَوۡاْ إِلَيۡكُمُ ٱلسَّلَمَ فَمَا جَعَلَ ٱللَّهُ لَكُمۡ عَلَيۡهِمۡ سَبِيلٗا ٩٠ سَتَجِدُونَ ءَاخَرِينَ يُرِيدُونَ أَن يَأۡمَنُوكُمۡ وَيَأۡمَنُواْ قَوۡمَهُمۡ كُلَّ مَا رُدُّوٓاْ إِلَى ٱلۡفِتۡنَةِ أُرۡكِسُواْ فِيهَاۚ فَإِن لَّمۡ يَعۡتَزِلُوكُمۡ وَيُلۡقُوٓاْ إِلَيۡكُمُ ٱلسَّلَمَ وَيَكُفُّوٓاْ أَيۡدِيَهُمۡ فَخُذُوهُمۡ وَٱقۡتُلُوهُمۡ حَيۡثُ ثَقِفۡتُمُوهُمۡۚ وَأُوْلَٰٓئِكُمۡ جَعَلۡنَا لَكُمۡ عَلَيۡهِمۡ سُلۡطَٰنٗا مُّبِينٗا ٩١

88. Shin me ya sa kuka kasu gida biyu dangane da lamarin munafuƙai, alhali Allah ne Ya mayar da su baya saboda abin da suka aikata? Shin kuna nufin ku shiryar da wanda Allah Ya riga Ya ɓatar da shi ne? Duk wanda Allah Ya ɓatar da shi kuwa, to ba za ka iya samar masa wata mafita ba.

89. Sun yi fatan ina ma za ku kafirta kamar yadda suka kafirta, sai ku zama ɗaya. Don haka kar ku riƙi masoya a cikinsu har sai sun yi hijira don Allah. Idan kuwa suka juya baya, to ku kama su, kuma ku kashe su a duk inda kuka same su; kuma kada ku riƙi wani masoyi ko mai taimako daga cikinsu.

90. Sai dai (ban da) waɗanda suke fakewa a wajen waɗansu mutane da kuke da yarjejeniya ta zaman lafiya a tsakaninku (da su), ko kuma waɗanda suka zo muku zukatansu sun ƙuntata game da yaƙar ku ko yaƙar mutanensu. Da kuwa Allah Ya ga dama da Ya ɗora su a kanku, kuma tabbas da sun yaƙe ku. Don haka idan suka bar ku ba su yaƙe ku ba, kuma suka miƙa muku saƙo na sulhu, to Allah bai ba ku wata dama ta ku yaƙe su ba.

91. Za ku sami wasu mutanen suna ƙoƙarin su sami amincewarku, kuma su sami amincewar mutanensu, amma duk sa'adda aka kira su zuwa kafirci sai su auka cikinsa. To idan ba su rabu da ku ba, kuma ba su neme ku da zaman lafiya ba, kuma ba su kame hannayensu ba, to ku kama su, kuma ku kashe su a duk inda kuka same su. Waɗannan kuwa Mun sanya muku bayyananniyar hujja a kansu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana magana da muminai a kan yadda suka rabu gida biyu dangane da sha'anin munafuƙai; wasu daga cikinsu suna kafirta su, wasu kuma ba sa kafirta su, alhalin Allah ya riga ya mayar da waɗannan munafuƙai sun dulmiya cikin kafirci saboda laifin da suka aikata, don haka bai dace a riƙa shakka game da kafircinsu ba. Ko kuma su masu shakkar kafircinsu suna nufin za su iya shiryar da wanda Allah bai nufe shi da shiriya ba? To duk wanda Allah ya riga ya ɓatar da shi, ba za ka iya samar masa wata hanyar shiriya ba.

An karɓo daga Zaidu ɗan Sabit (Allah ya ƙara masa yarda), ya ce game da faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): "Shin me ya same ku kuka kasu gida biyu dangane da lamarin munafuƙai?" Ya ce: "Wasu mutane da suka gudu daga yaƙin Uhudu, sai sahabbai suka kasu gida biyu dangane da lamarinsu, wasu suka ce kawai Annabi (ﷺ) ya kashe su, wasu kuma suka ce, a'a, kada ya kashe su. Sai wannan ayar ta sauka." [Bukhari #4050].

Annabi (ﷺ) dai bai kashe su ba don gudun kada a yaɗa ji ta-ji tar cewa Annabi (ﷺ) yana kashe sahabbansa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, su fa waɗannan munafuƙai, so suke yi muminai su kafirta kamar yadda su ma suka kafirta, duk su zama ɗaya. Sannan kuma Allah ya hana muminai su riƙi munafuƙai masoya, har sai sun tuba sun yi hijira saboda Allah, sun bar garuruwan kafirci inda ba a barin su su yi bautar Allah, sun ɗawo cikin muminai; wannan shi ne zai tabbatar da cewa sun tuba sun yi imani na gaskiya. Idan kuwa har suka bijire, suka ƙi yin imani, suka ƙi yin hijira, to muminai su yaƙe su, su kama su a matsayin fursunonin yaƙi, su kashe su duk inda suka same su, kada kuma su ƙulla wata soyayya da ɗaya daga cikinsu, kada kuma su riƙi wani a cikinsu a matsayin mai taimakon su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya keɓance wasu ɓangarori biyu daga cikin munafuƙai, ya hana a yaƙe su. Su ne:
• Waɗanda suka koma cikin kafirai waɗanda Musulmi suka yi sulhun dakatar da yaƙi a tsakaninsu da su, to sai a ƙyale su, kada a yaƙe su.
• Waɗanda suka kawo kansu ga muminai, suka nuna ba za su yaƙe su ba, kuma ba za su yi yaƙi tare da su ba, to su ma sai a bar su kada a yaƙe su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da cewa, da ya ga dama da sai ya ɗora waɗannan munafuƙai a kan muminai, su yaƙe su, sai dai Allah cikin luɗufinsa da rahmarsa, ya dankwafar da su, ya hana musu yaƙar muminai. Idan munafuƙai suka ƙyale muminai suka yi sulhu da su na zaman lafiya, to bai halatta ga muminai su kashe su ba, ko su ci ganimar dukiyoyinsu, ko su kama matansu da 'ya'yansu a matsayin bayi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ci gaba da bayyana wa muminai cewa, za su ci karo da wasu munafuƙai na daban, waɗanda suke son su zauna lafiya da Musulmi, don haka sai su riƙa nuna su ma Musulmi ne, amma kuma ta ɓangare guda suna son su zauna da 'yan'uwansu kafirai lafiya, to sai su riƙa bauta wa abin da mutanensu kafirai suke bauta wa, duk sa'adda aka gayyace su zuwa ga wani aiki na kafirci ko shirka, nan da nan sai su amsa kira, don haka suka daɗa nutsuwa sosai cikin kafirci da shirka.
To wannan nau'i na munafunci in har ba su bar yaƙar muminai ba, suka zaɓi zaman lafiya da su, to muminai su yaƙe su, su kama su fursunoni, su kashe su duk inda suka same su. Allah ya bai wa muminai hujja ƙarara ta yaƙar su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mai imani na ƙwarai ba zai kashe ɗan'uwansa mumini ba.

2. Girman sha'anin kisan kai. Don haka Allah ya wajabta yin kaffara a kansa, tare da cewa a ƙa'idar shari'a babu kaffara a kan wanda ya yi kuskure, domin an ɗauke alƙalami daga kansa.

3. Falalar yin afuwa da yafiya. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amabaci afuwa da sunan sadaka.

4. Musulunci yana son samar da yarda da juna a tsakanin 'ya'yansa, don haka yake toshe duk wata ƙofa ta zargi da rashin amince wa juna, domin duk wanda ya riƙa zargin mutane, to shi ma wata rana za a zarge shi.

5. Taka-tsantsan wajibi ne a kowane lokaci, kuma a kowane wuri, hatta a lokacin yaƙi. Domin taka-tsantsan yana hana aukuwar matsaloli da dama da tabbatar da maslaha a kowane lokaci.

6. Jin daɗin duniya wani abu ne marar tabbas, kuma mai gushewa nan da nan. Ni'imar lahira ita ce ni'ima mai ɗorewa ta har abada.

7. Lalle ya kamata bawa idan ya ga zuciyarsa tana karkata ga abin da bai dace ba, to ya tunatar da ita abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanada ga wanda zai saɓa wa son zuciyarsa, ya zaɓi yardar Allah fiye da yardarsa; yin haka zai ƙara kwaɗaitar da shi wajen aikata abin da Allah ya umarce shi da shi komai wahalarsa.

8. Idan mutum ya yi niyyar zargin wani a kan wata halayya, to ya tuna yadda shi yake a da kafin Allah ya yi masa baiwa ya zama yadda yake a yanzu, kamar malami da ɗalibinsa, ko shugaba da talakawansa, ko uba da ɗansa, ko babban ma'aikaci da ƙarami.

9. Musulunci ya hana kashe wanda ya bayyana Musuluncinsa a zahiri ko ya yi sallama. Haka nan ya hana kashe waɗanda tsakaninsu da Musulmi akwai sulhu na zaman lafiya, ko alƙawari da yarjejeniya, ko amana ta zamantakewa, da wanda bai taya mutanensa yaƙar Musulmi ba. Sannan Musulunci ya soki duk wanda zai yi yaƙi don abin duniya da kwasar ganima. Ya yi umarni da yaƙi ne don tabbatar da gyara cikin al'umma da kawar da zalunci da kafa adalci. Saɓanin yadda a yanzu ake yaƙi don kwashe arzikin wata ƙasa da shimfiɗa mulkin duniya da kama-karya a kan raunana marasa ƙarfi.

Suratun Nisa'i (92-94)

وَمَا كَانَ لِمُؤۡمِنٍ أَن يَقۡتُلَ مُؤۡمِنًا إِلَّا خَطَـٔٗاۚ وَمَن قَتَلَ مُؤۡمِنًا خَطَـٔٗا فَتَحۡرِيرُ رَقَبَةٖ مُّؤۡمِنَةٖ وَدِيَةٞ مُّسَلَّمَةٌ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِۦٓ إِلَّآ أَن يَصَّدَّقُواْۚ فَإِن كَانَ مِن قَوۡمٍ عَدُوّٖ لَّكُمۡ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَتَحۡرِيرُ رَقَبَةٖ مُّؤۡمِنَةٖۖ وَإِن كَانَ مِن قَوۡمِۭ بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَهُم مِّيثَٰقٞ فَدِيَةٞ مُّسَلَّمَةٌ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِۦ وَتَحۡرِيرُ رَقَبَةٖ مُّؤۡمِنَةٖۖ فَمَن لَّمۡ يَجِدۡ فَصِيَامُ شَهۡرَيۡنِ مُتَتَابِعَيۡنِ تَوۡبَةٗ مِّنَ ٱللَّهِۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ٩٢ وَمَن يَقۡتُلۡ مُؤۡمِنٗا مُّتَعَمِّدٗا فَجَزَآؤُهُۥ جَهَنَّمُ خَٰلِدٗا فِيهَا وَغَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ وَلَعَنَهُۥ وَأَعَدَّ لَهُۥ عَذَابًا عَظِيمٗا ٩٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا ضَرَبۡتُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَتَبَيَّنُواْ وَلَا تَقُولُواْ لِمَنۡ أَلۡقَىٰٓ إِلَيۡكُمُ ٱلسَّلَٰمَ لَسۡتَ مُؤۡمِنٗا تَبۡتَغُونَ عَرَضَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا فَعِندَ ٱللَّهِ مَغَانِمُ كَثِيرَةٞۚ كَذَٰلِكَ كُنتُم مِّن قَبۡلُ فَمَنَّ ٱللَّهُ عَلَيۡكُمۡ فَتَبَيَّنُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٗا ٩٤

92. Kuma bai dace ga mumini ya kashe wani mumini ba, sai bisa kuskure. Wanda ya kashe mumini bisa ga kuskure, to zai ‘yanta bawa ko baiwa mumina da kuma diyya wadda za a miƙa wa iyalinsa, sai fa idan sun yafe. Amma idan wanda aka kashe yana cikin mutanen da suke maƙiyanku, alhalin kuma shi mumini ne, to za ku ‘yanta bawa ko baiwa mumina; idan kuwa ya kasance yana cikin mutanen da kuke da yarjejeniyar zaman lafiya da su, to za a bayar da diyya wadda za a miƙa wa iyalinsa, sannan za ku ‘yanta bawa ko baiwa mumina; wanda kuwa bai sami ikon haka ba, to sai ya yi azumin wata biyu a jere don tuba zuwa ga Allah. Allah kuwa Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima.

93. Duk kuwa wanda ya kashe mumini da gangan, to sakamakonsa wutar Jahannama ce, yana mai dawwama a cikinta, kuma Allah Ya yi fushi da shi, kuma Ya la’ance shi, kuma Ya yi masa tanadin azaba mai girma.

94. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka fita yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah, to ku riƙa bincike, kuma kada ku ce ma wanda ya yi muku sallama: “Kai ba mumini ba ne,” don kawai kuna neman wani jin daɗi na rayuwar duniya, to a wurin Allah ne ganimomi masu yawa suke. Kamar haka ku ma a da kuka kasance, sai Allah Ya yi muku baiwa, don haka ku riƙa bincike. Lalle Allah Ya kasance Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukunce-hukuncen shari’a dangane da kisa na kuskure da kuma kisa na gangaci. Kisan kuskure shi ne kamar mutum ya nufi harbin wani abin farauta, sai ya harbe mutum ya mutu. Shi ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, bai halatta mumini ya kashe ɗan’uwansa mumini ba, sai ta hanyar kuskure ba da niyya ba. To idan haka ta faru, sai wanda ya yi kisan ya yi kaffara ta hanyar ‘yanta bawa mumini ko baiwa mumina, kuma dole ya biya diyya cikakkiya, wadda shi da danginsa za su ɗauki nauyin biya, a bayar da ita ga magadan wanda aka kashe, sai dai idan sun yafe masa ita, to shi ke nan ba ta zama wajibi a kansa ba.
To idan wanda aka kashe mumini ne, amma mutanensa kafiran yaƙi ne, to wanda ya yi kisan zai ‘yanta bawa ne mumini ko baiwa mumina kawai. Idan kuwa muminin da aka kashe ya fito ne daga mutanen da suke kafiran amana ne ko an yi sulhu da su, babu yaƙi tsakaninsu da muminai, to dole ne wanda ya yi kisa ya biya diyya ga magadan wanda ya kashe, kuma ya ‘yanta bawa mumini ko baiwa mumina. Wanda bai sami bawa ko baiwar da zai ‘yanta ba, ko ba shi da kuɗin sayen ta, to wajibi ne ya yi azumin wata biyu a jere. Allah ya shar’anta wa bayinsa waɗannan hukunce-hukunce don su zama tuba gare su da rahama, kuma Allah mai cikakken sani ne, kuma gwani mai hikima.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin narko mai tsanani ga wanda ya yi kisan kai na gangaci. Allah ya yi alƙawarin shigar da shi Jahannama, ya dawwama a cikinta, kuma Allah ya yi fushi da shi, sannan ya la’ance shi, baya ga haka kuma ya yi masa tanadin azaba mai girman gaske.
Sai Allah ya umarci muminai da lalle su yi taka-tsantsan wajen kashe rai, ko da kuwa sun fita wajen yaƙi ne. Duk sanda suke shakka game da kafircin wani, to kada su kuskura su kashe shi, har sai sun sami tabbacin shi kafiri ne. Kada wani ya bayyana musu Musuluncinsa, ya miƙa wuya gare su, ba tare da ya yaƙe su ba, sannan su ce ai shi ba Musulmi ne ba. Su yi aiki da abin da ya bayyana na halinsa, kada su kashe shi don neman abin duniya, wato su karɓe dukiyar da ke tare da shi. Allah ya tunatar da su cewa, su ma fa a da haka suke, suna ɓoye imaninsu daga mutanensu mushirikai, sai Allah ya yi musu baiwa, ya ƙarfafa addininsu, har suka wayi gari suna iya bayyana Imaninsu da suke ɓoyewa. Don haka wajibi ne a kansu su yi bincike kafin su kashe wanda suke shakka a kan lamarinsa, Allah kuwa yana sane da duk abin da suke aikatawa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Musulmi sun fito yaƙi, sai suka ci karo da wani mutum yana kiwon dabbobinsa. Da ya gan su sai ya ce musu: “Assalamu alaikum.” Duk da

haka sai suka kashe shi, suka kwashe dabbobinsa." Sai Allah ya saukar da wannan ayar." [Bukhari #4591, da Muslim #3025].

Usamatu ɗan Zaidu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya tura mu zuwa ga wata ƙabila mai suna *Alhuraka*, wani sashe na ƙabilar *Juhainah*, sai muka yi wa waɗannan mutanen dirar mikiya da sassafe, muka fatattake su." Usamatu ya ce: "Sai ni da wani mutumin Madina muka bi wani mutum daga cikinsu, yana ganin mun cim masa, sai ya ce: *"La ilaha illal lahu."* Usamatu ya ce: "Sai wannan mutumin Madina ya rabu da shi, amma ni sai na soke shi da mashina, na kashe shi. To lokacin da muka dawo, labari ya je wa Annabi (ﷺ), sai ya ce: "Yanzu Usamatu kashe shi ka yi bayan ya ce: *"La ilaha illal lahu*."? Sai Usamatu ya ce: "Ya faɗe ta ne don kawai ya kare kansa." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya sake cewa: "Yanzu Usamatu kashe shi ka yi bayan ya ce: *"La ilaha illal lahu."*? Usamatu ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) bai gushe ba yana maimaita mini wannan kalma, har sai da na yi burin ina ma ban musulunta ba kafin wannan rana." [Bukhari #6872, da Muslim #96].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutane ba matsayi ɗaya suke a wurin Allah ba, Allah yana fifita wasu a kan wasu da darajoji masu yawa.

2. Falalar jihadi da dukiya da rayuka.

3. Wanda bai fita jihadi ba saboda rashin lafiya ko wata larura, to yana daidai da wanda ya fita wajen samun lada, matuƙar dai ya yi tarayya da shi a niyya.

4. Jihadi farlu kifaya ne, ba an wajabta shi a kan kowane mumini ba, don haka ne Allah ya yi alƙawarin Aljanna ga waɗanda suka fita jihadi da waɗanda ba su fita ba.

Suratun Nisa'i (95-96)
لَّا يَسْتَوِي ٱلْقَٰعِدُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ غَيْرُ أُوْلِي ٱلضَّرَرِ وَٱلْمُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ ۚ فَضَّلَ ٱللَّهُ ٱلْمُجَٰهِدِينَ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ عَلَى ٱلْقَٰعِدِينَ دَرَجَةً ۚ وَكُلًّا وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ وَفَضَّلَ ٱللَّهُ ٱلْمُجَٰهِدِينَ عَلَى ٱلْقَٰعِدِينَ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿٩٥﴾ دَرَجَٰتٍ مِّنْهُ وَمَغْفِرَةً وَرَحْمَةً ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٩٦﴾

95. Waɗanda suka zauna a gida daga cikin muminai ba su fita yaƙi ba, in dai ba masu larura ba, ba za su yi daidai da masu jihadi don ɗaukaka kalmar Allah da dukiyoyinsu da kawunansu ba. Allah Ya fifita darajar masu jihadi da dukiyoyinsu da kawunansu a kan waɗanda suka zauna a gida. Kuma dukkansu Allah Ya yi masu alƙawarin Aljanna. Kuma Allah Ya fifita masu jihadi a kan waɗanda suka zauna a gida, da lada mai girma.

96. Wasu darajoji masu yawa daga gare Shi da gafara da kuma jin ƙai. Kuma Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana falalar masu fita jihadi don ɗaukaka kalmarsa, watau yadda ya fifita darajarsu da matsayinsu a wurinsa. Allah ya nuna cewa, wanda zai fita jihadi don Allah da dukiyarsa da ransa, ba za a daidaita shi da wanda ya yi zamansa gida bai fita ba, kuma ba don yana tare da wata larura ba, kamar makanta ko gurgunta ko rashin lafiya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fifita masu jihadi a kan waɗanda ba sa jihadi da wani lada mai girma. Amma su duka masu

jihadin da waɗanda ba sa jihadi, Allah ya yi musu alƙawarin gidan Aljanna, sai dai kuma a Aljannar Allah ya fifita masu jihadi da wasu darajoji maɗaukaka da zai ɗaukaka su da su a Aljanna tare da gafarar zunubansu da samun rahamar Ubangijinsu. Allah kuwa mai yawan gafara ne, mai jin ƙai.

An karɓo daga Zaidu ɗan Sabitu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Manzon Allah (ﷺ) ya yi masa shiftar wannan ayar kamar haka: “Waɗanda suke zaune a gida ba su fita yaƙi ba daga cikin muminai, ba za su yi daidai da masu jihadi don ɗaukaka kalmar Allah ba.” Yana cikin karanto mini wannan ayar sai Abdullahi ɗan Ummu Maktum ya zo, sai ya ce: “Ya Manzon Allah, da zan iya yin jihadi da na yi.” Shi kuwa makaho ne. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Manzonsa faɗarsa: “Ban da masu larura.” A lokacin cinyarsa tana kan cinyata, sai ta yi mini nauyin gaske, har sai da na ji tsoron kada cinyata ta dagargaje. Sannan sai aka yaye masa.” [Bukhari #2832].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Wanda ya yi imani da Allah da Manzonsa, kuma ya tsayar da salla, ya yi azumin watan Ramadana, to haƙƙi ne a kan Allah ya shigar da shi Aljanna, daidai ne ya yi hijira domin Allah, ko ya yi zamansa a ƙasar haihuwarsa.” Sai sahabbai suka ce: “Ya Manzon Allah (ﷺ), yanzu ba ma faɗa wa mutane haka ba?” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “A cikin Aljanna akwai matakai na daraja ɗari, waɗanda Allah ya tanade su ne ga masu jihadi, tsakanin kowane mataki da na biye da shi, kamar tsakanin sama ne da ƙasa, don haka idan za ku roƙi Allah, to ku roƙe shi Aljannar Firdausi, domin ita ce mafi ɗaukaka, samanta Al-Arshin Allah mai rahama ne, daga nan ƙoramun gidan Aljanna suke ɓuɓɓugowa.” [Bukhari #7423, da Muslim #1884].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin yin hijira daga wurin da ake hana wa Musulmi bautar Allah, zuwa inda zai bauta masa ba tare da wata tsangwama ba.

2. Wanda ya ci gaba da zama a wurin da ba za a bar shi ya bauta wa Allah ba, tare da cewa yana da halin yin ƙaura zuwa cikin ‘yan’uwansa Musulmi, to wannan ba shi da wani uzuri a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Amma wanda aka hana shi yin hijirar, ko ba shi da ikon yin ta, to wannan wajabcin hijirar ya faɗi daga kansa.

3. Duk wanda ya yi yunƙurin yin aiki na ƙwarai, sai wani uzuri ya hana shi, to zai sami ladansa cikakke a wurin Allah.

Suratun Nisa’i (97-100)

إِنَّ ٱلَّذِينَ تَوَفَّىٰهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ ظَالِمِيٓ أَنفُسِهِمۡ قَالُواْ فِيمَ كُنتُمۡۖ قَالُواْ كُنَّا مُسۡتَضۡعَفِينَ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ قَالُوٓاْ أَلَمۡ تَكُنۡ أَرۡضُ ٱللَّهِ وَٰسِعَةٗ فَتُهَاجِرُواْ فِيهَاۚ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۖ وَسَآءَتۡ مَصِيرًا ٩٧ إِلَّا ٱلۡمُسۡتَضۡعَفِينَ مِنَ ٱلرِّجَالِ وَٱلنِّسَآءِ وَٱلۡوِلۡدَٰنِ لَا يَسۡتَطِيعُونَ حِيلَةٗ وَلَا يَهۡتَدُونَ سَبِيلٗا ٩٨ فَأُوْلَٰٓئِكَ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَعۡفُوَ عَنۡهُمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَفُوّٗا غَفُورٗا ٩٩ ۞وَمَن يُهَاجِرۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ يَجِدۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُرَٰغَمٗا كَثِيرٗا وَسَعَةٗۚ وَمَن يَخۡرُجۡ مِنۢ بَيۡتِهِۦ مُهَاجِرًا إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ يُدۡرِكۡهُ ٱلۡمَوۡتُ فَقَدۡ وَقَعَ أَجۡرُهُۥ عَلَى ٱللَّهِۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ١٠٠

97. Lalle waɗanda mala’iku suke karɓar rayukansu suna masu zaluntar kawunansu, (mala’ikun) za su ce (da su): “Cikin wane hali kuka kasance?” Sai su ce: “Mu mun kasance masu rauni a bayan ƙasa.” Sai su ce: “Ashe ƙasar Allah ba mai yalwa ba ce, ta yadda za ku sami damar yin hijira a cikinta?” To waɗannan, makomarsu ita ce wutar Jahannama, kuma wannan makoma ta munana.

98. Sai dai waɗanda suke raunana cikin maza da mata da yara ƙanana waɗanda ba su da wata dabara, kuma ba za su gane wata hanya (ta hijira) ba.

99. To waɗannan mai yiwuwa ne Allah Ya yi musu afuwa, Allah kuma Ya kasance Mai afuwa ne, Mai yawan gafara.

100. Kuma duk wanda ya yi hijira saboda Allah, zai samu wuraren hijira masu yawa da yalwa a bayan ƙasa. Kuma duk wanda ya fita daga gidansa, yana mai hijira zuwa ga Allah da Manzonsa, sannan mutuwa ta riske shi, to haƙiƙa ladansa ya tabbata a wajen Allah. Kuma Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana hukuncin waɗanda suka ƙi yin hijira su koma ƙasar Musulunci, suka ci gaba da zama a ƙasar kafirci, tare da cewa suna iya fita su yi hijirar, a inda suke kuma kafirai ba za su ƙyale su su tsayar da ibadun Musulunci yadda suke so ba. To shi ne Allah yake zargin masu wannan hali, yana bayyana musu haɗarin da suke ciki, musamman lokacin da mala'iku za su zo karɓar rayukansu, su ce musu: "Me ya sa kuka ci gaba da zama a cikin irin wannan hali?" Sai suka amsa musu da cewa: "Mu masu rauni ne, mun kasa fita mu yi hijira mu bi 'yan'uwanmu Musulmi." Sai mala'iku su mayar musu da cewa: "Ashe ƙasar Allah ba mai yalwa ce ba? Me ya sa ba ku tafi zuwa wani wuri ba inda za ku iya bautar Allah a can?" Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan mutane da za su mutu a cikin irin wannan hali, to makomarsu Jahannama ce, kuma wannan makoma tasu ta yi muni.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wasu Musulmi sun ci gaba da zama cikin mushirikai, idan sun fita yaƙi suna fita da su, su ƙara musu yawan jama'a. To wani lokaci idan aka harbo kibiya sai ta sami wani daga cikinsu ta kashe, ko a sari wani a kashe shi. Sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Lalle waɗanda mala'iku suke karɓar rayukansu suna masu zaluntar kawunansu...." [Bukhari #7085].

Amma kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi togaciya ta waɗanda suke raunana ne maza da mata da yara, waɗanda kafirai suka hana su fita su yi hijira, su kuma ba su da wata dabara da za su iya yi su yi hijira, ba su da wata hanya da za su kuɓutar da kansu daga hannun mushirikai. To waɗannan Allah ya yafe musu, ba zai kama su da laifin ƙin yin hijira ba. Kuma Allah mai yawan gafara ne, mai yawan jin ƙai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) yana cewa game da faɗar Allah: "Sai dai waɗanda suke raunana..." Ya ce: "Ni da mahaifiyata muna daga cikin waɗanda Allah ya yi musu uzuri." [Bukhari #4597].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance idan ya ɗago daga ruku'u a raka'arsa ta ƙarshe a sallar Isha'i, bayan ya ce: *"Sami' Allahu liman hamidah."* Sai ya ce: "Ya Allah ka kuɓutar da Ayyashu ɗan Rabi'atu, ya Allah ka kuɓutar da Alwalidu ɗan Alwalidu, ya Allah ka kuɓutar da Salamatu ɗan Hisham, ya Allah ka kuɓutar da muminai masu rauni, ya Allah ka tsananta uƙubarka a kan mutanen Makka, ya Allah ka jarrabe su da fari irin farin da ka jarrabi mutanen Annabi Yusufu da shi." [Bukhari #6393, da Muslim #675].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar a kan yin hijira, inda ya bayyana cewa wanda duk ya yi hijira domin Allah, to zai sami wuraren hijira masu yawa da yalwa a bayan ƙasa, inda zai iya bautar Allah cikin tsanaki, ba tare da tsangwama ba, kuma ya sami abin da zai ci, ya sha, da sauran buƙatunsa na rayuwa.

Amma wanda ya fita daga gidansa, ya bar ƙasarsa domin gudun hijira don Allah da Manzonsa (ﷺ), to amma kuma sai mutuwa ta riske shi kafin ya isa inda ya nufa, wato ƙasar Musulunci, to wannan ladansa ya tabbata a wurin Allah, kuma Allah mai gafara ne, mai jin ƙai.
Wannan ayar ta sauka bayan wani sahabi mai suna Dhamratu ɗan Jundubu ya fito daga gidansa, ya ce wa iyalansa: "Ku ɗauke ni ku fitar da ni daga ƙasar mushirikai, ku kai ni ga Manzon Allah (ﷺ)." Sai suka ɗauke shi, suka fita da shi. Sai ya mutu a hanya kafin ya ƙarasa wurin Manzon Allah (ﷺ), sai wannan ayar ta sauka. [Dubi At-Tabari, Tafsir 7:392, da Ibn Kasir, Tafsir 2:391].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin sauƙin addinin Musulunci da sauƙin hukunce-hukuncensa.

2. Koƙarin kafirai wajen su fitini Musulmi game da addininsu a koyaushe.

3. Kafirai maƙiya ne na zahiri ga muminai.

4. Bayanin girman sha'anin salla. Musulunci bai ɗauke ta daga kan Musulmi ba ko da a lokacin yaƙi da halin tsoro.

5. Wajabcin sallar jam'i. Domin Allah ya yi umarni da ita har a cikin yanayi na yaƙi, balle kuma a cikin yanayi na zaman lafiya. Sannan ya sarayar da wasu ayyuka na wajibi a salla da kuma yin afuwa ga yin wasu ayyuka masu ɓata salla, domin tabbatar da sallar jam'i. Ba a barin aikata wajibi domin tabbatar da mustahabbi kaɗai.

6. Umarni ga Musulmi su zama masu taka-tsantsan a kowanne lokaci, kada su saki jiki maƙiyansu su yi musu ba-zata.

7. Idan an hore mu da ambaton Allah a kowanne hali muke ciki lokacin yaƙi, to babu shakka mu zamanto masu ambaton Allah a lokacin zaman lafiya shi ya fi cancanta, domin mumini a koyaushe cikin fafatawa yake da maƙiyansa na sarari, da na ɓoye, wato soye-soyen zuciyarsa.

8. Umarni da ambaton Allah bayan aukuwar yanayi na tsoro da fargaba, wato bayan kammala sallar tsoro, yana nuni da cewa, zuciya takan karaya, ta yi rauni, yayin da tsoro da fargaba suka shige ta. Don haka babu abin da zai farfaɗo da ita, ya ƙarfafe ta, sai ambaton Allah, shi ya sa Allah ya yi umarni da yin sa a wannan wuri.

9. Muminai idan wata musifa ta same su, to sukan karɓe ta da yarda da kuma neman kyakkyawan sakamako daga Allah. Idan yardar ta kuɓuce musu, to sukan yi haƙuri da kuma fatan samun lada daga Allah. Wannan shi ne abin da yake rage musu raɗaɗin musifar. Kafirai kuwa babu wata yarda tare da su, babu fatan samun lada daga Allah, idan kuma sun yi haƙuri, to irin haƙurin dabbobi ne.

10. Ya kamata ga mutum idan ya yi kyakkyawan aiki, to ya yi fatan samun sakamakon ladan aikinsa daga Allah.

وَإِذَا ضَرَبْتُمْ فِي ٱلْأَرْضِ فَلَيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ أَن تَقْصُرُواْ مِنَ ٱلصَّلَوٰةِ إِنْ خِفْتُمْ أَن يَفْتِنَكُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِنَّ ٱلْكَٰفِرِينَ كَانُواْ لَكُمْ عَدُوًّا مُّبِينًا ﴿١٠١﴾ وَإِذَا كُنتَ فِيهِمْ فَأَقَمْتَ لَهُمُ ٱلصَّلَوٰةَ فَلْتَقُمْ طَآئِفَةٌ مِّنْهُم مَّعَكَ وَلْيَأْخُذُوٓاْ أَسْلِحَتَهُمْ ۖ فَإِذَا سَجَدُواْ فَلْيَكُونُواْ مِن وَرَآئِكُمْ وَلْتَأْتِ طَآئِفَةٌ أُخْرَىٰ لَمْ يُصَلُّواْ فَلْيُصَلُّواْ مَعَكَ وَلْيَأْخُذُواْ حِذْرَهُمْ وَأَسْلِحَتَهُمْ ۗ وَدَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوْ تَغْفُلُونَ عَنْ أَسْلِحَتِكُمْ وَأَمْتِعَتِكُمْ فَيَمِيلُونَ عَلَيْكُم مَّيْلَةً وَٰحِدَةً ۚ وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ إِن كَانَ بِكُمْ أَذًى مِّن مَّطَرٍ أَوْ كُنتُم مَّرْضَىٰٓ أَن تَضَعُوٓاْ أَسْلِحَتَكُمْ ۖ وَخُذُواْ حِذْرَكُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ أَعَدَّ لِلْكَٰفِرِينَ عَذَابًا مُّهِينًا ﴿١٠٢﴾ فَإِذَا قَضَيْتُمُ ٱلصَّلَوٰةَ فَٱذْكُرُواْ ٱللَّهَ قِيَٰمًا وَقُعُودًا وَعَلَىٰ جُنُوبِكُمْ ۚ فَإِذَا ٱطْمَأْنَنتُمْ فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ ۚ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ كَانَتْ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ كِتَٰبًا مَّوْقُوتًا ﴿١٠٣﴾ وَلَا تَهِنُواْ فِي ٱبْتِغَآءِ ٱلْقَوْمِ ۖ إِن تَكُونُواْ تَأْلَمُونَ فَإِنَّهُمْ يَأْلَمُونَ كَمَا تَأْلَمُونَ ۖ وَتَرْجُونَ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا يَرْجُونَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿١٠٤﴾

101. Kuma idan kun yi tafiya a bayan ƙasa, to babu laifi a kanku ku yi sallar ƙasaru, in kun ji tsoron kafirai su fitine ku. Lalle kafirai sun kasance maƙiya ne, masu bayyana ƙiyayya a gare ku.

102. Kuma idan ka kasance a cikinsu, sai ka yi musu limancin salla, to sai wata ƙungiya su tsaya tare da kai, kuma su riƙe makamansu, to yayin da suka yi sujada (wato salla), sai su koma bayanku, sai ɗaya ƙungiyar wadda ba su yi salla ba, su zo su yi salla tare da kai, kuma su ma su yi taka-tsantsan, su kuma riƙe makamansu. Kafirai kuwa suna burin ina ma za ku gafala ku ajiye makamanku da kayayyakin guzurinku, sai su far muku gaba ɗaya. Kuma idan akwai wata cuta tare da ku saboda ruwan sama ko kun kasance marasa lafiya, to babu laifi a gare ku ku ajiye makamanku, amma fa ku yi taka-tsantsan. Lalle Allah Ya yi wa kafirai tanadin wata azaba mai wulaƙantarwa.

103. To idan kun kammala salla, to sai ku ambaci Allah a tsaye ko a zaune ko kuma a kwance. To idan kuka samu nutsuwa sai ku tsayar da salla (a yadda take). Lalle salla ta kasance wata farilla ce mai ƙayyadajjen lokaci a kan muminai.

104. Kuma kada ku yi rauni wajen neman mutanen; in kun kasance kuna jin raɗaɗi, to ai su ma (kafirai) suna jin raɗaɗi kamar yadda kuke jin raɗaɗi; kuma kuna fatan wani lada a wurin Allah, wanda su ba sa fatan irinsa. Allah kuwa Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai yawan hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara bayanin halaccin sallar ƙasaru ga matafiya. Sallar ƙasaru ita ce rage salloli masu raka’a huɗu su koma biyu. Allah ya bayyana cewa yin haka babu wani laifi ga matafiyi. Ko da yake ayar ta ambaci halin tsoron fitinar kafirai, to amma wannan ba sharaɗi ba ne, duk wanda yake cikin halin tafiya, an yi masa rangwamen yin sallar ƙasaru.

An karɓo daga Ya’ala ɗan Umayya (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, na tambayi Umar ɗan Khattab (Allah ya ƙara masa yarda) game da faɗar Allah: “Babu laifi a kanku ku yi sallar ƙasaru in kun ji tsoron kafirai su fitine ku.” Ya ce: “To ga shi yanzu mutane sun aminta, babu wani tsoro.” Sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce masa: “Ni ma na yi mamakin wannan abu kamar yadda ka yi mamaki, sai na tambayi Manzon Allah (ﷺ), sai ya ce: “Sadaka ce Allah ya ba ku, don haka ku karɓi sadakarsa.” [Muslim #686, da Abu Dawud #1199, da Ibn Maja #1065, da Ahmad #178].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin sallar tsoro, ya bayyana wa Annabinsa (ﷺ) yadda zai yi limancin salla da sahabbansa a lokacin da ake cikin halin yaƙi. Ya umarce su da su rabu kaso biyu, kashi na farko su shiga salla tare da Annabi (ﷺ), yayin da ɗaya kashin suna bayansu da makamansu, suna kare masu salla. Idan Annabi (ﷺ) ya yi raka’a ɗaya da su, sai ya tsaya a tsaye, su kuma sai su cika

raka’a ɗayar, su yi sallama, su koma baya su canji masu kare su, su kuma waɗancan da ba su yi salla ba, sai su zo su shiga salla tare da Annabi (ﷺ), ya yi raka’arsa ɗaya da ta rage masa tare da su; idan ya yi sallama, sai su tashi su ciko raka’a ɗaya, su zauna su yi tahiya, su yi sallama. A duk cikin wannan yanayi kada su yi sakaci da riƙe makamansu.
Sunnar Annabi (ﷺ) ta zo da bayanin wata hanyar daban ta sallar tsoro.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai sun yi burin ina ma muminai za su shagala da salla, su bar makamansu da kayayyakin guzurinsu, su kuma su auko musu gaba ɗaya su murƙushe su. To amma idan an sami wani uzuri da zai hana wasu ɗaukar makami domin sun yi musu nauyi, kamar wanda ruwa ya doke shi har ya sa masa rashin lafiya, ko kuma ba shi da lafiyar, to babu laifi ya ajiye makaminsa, amma duk da haka lalle su yi taka-tsantsan. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ya tanadar wa kafirai azaba ta wulaƙanci duniya da lahira.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Musulmi yayin da suka gama sallar tsoro, da cewa su ambaci Allah, a tsaye suke ko a zaune ko a kwance. Idan sun fita daga cikin halin tsoro, sun sami aminci, sai su yi cikakkiyar salla, domin kuwa salla wani farali ne mai lokaci ƙayyadadde a wurin Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Musulmi kashedi da kada su zama raunana ko masu kasala wajen neman maƙiyansu a fagen yaƙi. Kada rauni da zai sami wasu daga cikinsu ya sare musu gwiwa, domin idan har su muminai suna jin zafin kisa ko raunin da ya same su, to ai su ma kafiran suna jin zafin abin da yake samun su na kisa ko rauni. To amma su muminai sun fi su nesa ba kusa ba, domin suna sa ran samun wani lada da tagomashi daga Allah na cin nasara da taimakon addininsa, wanda su kafirai ba su da wannan tsammanin. Don haka su muminai ya kamata su zage dantse wajen taimakon addinin Allah, su bar kasala da mutuwar jiki. Lalle Allah mai cikakken ilimi ne game da duk halin da suke ciki, kuma mai hikima ne cikin duk abin da ya shar’anta musu ko ya ƙaddara musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani hukunci daga Allah yake, babu wanda zai iya kauce wa wani hukunci na Allah don ya yardar da wani ko ya daɗaɗa masa.

2. Haramcin taimaka wa mai laifi a kan laifinsa.

3. Yi wa Musulmi kashedi a kan ya guji taimaka wa wani azzalumi a kan zaluncinsa.

4. Hana ba wa maciya amana kariya doka ce ta Allah da ta shafi dukkan bayinsa, domin maciya amana akwai su a kowanne zamani da kowanne wuri. Hikimar fuskantar da hanin ga Manzon Allah (ﷺ) ita ce domin a fito da girman lamarin a fili.

5. Duk wanda ya cuci wani ko ya ci amanarsa, to kansa ya cuta, kuma ya ci amanar kansa ne.

6. Cin amana yana daga cikin manya-manyan laifuka.

7. Duk wani mai son aikata laifi ya kamata ya tuna, cewa, Allah yana ganin sa, ko da kuwa ba wanda ya gan shi duk duniya. Wannan zai sa ya ji tsoron Allah, ya janye.

8. Gargaɗi ga lauyoyi Musulmi da su guji kare wanda suka fahimci shi mai laifi ne, domin kare shi goyon bayan ɓarna da rashin gaskiya ne, wanda kuma haramun ne a Musulunci.

إِنَّآ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ لِتَحۡكُمَ بَيۡنَ ٱلنَّاسِ بِمَآ أَرَىٰكَ ٱللَّهُۚ وَلَا تَكُن لِّلۡخَآئِنِينَ خَصِيمٗا ١٠٥ وَٱسۡتَغۡفِرِ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ١٠٦ وَلَا تُجَٰدِلۡ عَنِ ٱلَّذِينَ يَخۡتَانُونَ أَنفُسَهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ مَن كَانَ خَوَّانًا أَثِيمٗا ١٠٧ يَسۡتَخۡفُونَ مِنَ ٱلنَّاسِ وَلَا يَسۡتَخۡفُونَ مِنَ ٱللَّهِ وَهُوَ مَعَهُمۡ إِذۡ يُبَيِّتُونَ مَا لَا يَرۡضَىٰ مِنَ ٱلۡقَوۡلِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِمَا يَعۡمَلُونَ مُحِيطًا ١٠٨ هَٰٓأَنتُمۡ هَٰٓؤُلَآءِ جَٰدَلۡتُمۡ عَنۡهُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا فَمَن يُجَٰدِلُ ٱللَّهَ عَنۡهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ أَم مَّن يَكُونُ عَلَيۡهِمۡ وَكِيلٗا ١٠٩

105. Lalle Mu Mun saukar maka da Littafi da gaskiya domin ka yi hukunci a tsakanin mutane da abin da Allah Ya sanar da kai, kuma kada ka zamo mai ba da kariya ga maha’inta.

106. Kuma ka roki gafarar Allah, lalle Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin kai.

107. Kuma kada ka kare waɗanda suke ha’intar kawunansu. Lalle Allah ba Ya son duk wanda ya kasance mai yawan ha’inci ne, mai yawan saɓo.

108. Suna ɓoye wa mutane (laifinsu), amma ba sa ɓoye wa Allah, alhali kuwa Yana tare da su yayin da suke kwana suna ƙulle-ƙullen maganar da bai yarda da ita ba. Kuma lalle Allah Ya kasance Mai kewayewa ne ga abin da suke aikatawa.

109. Sai ga shi ku waɗannan kun ba su kariya a rayuwar duniya, to wane ne zai ba su kariya a gaban Allah a ranar alƙiyama, ko kuwa wane ne zai zama wakilinsu?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabinsa (ﷺ) cewa, shi ne ya saukar masa da littafi da gaskiya, wanda kuma ya ƙunshi gaskiya tsantsa, domin ya yi wa mutane hukunci da abin da Allah ya sanar da shi daga wannan littafi. Kuma kada ya kuskura ya zama mai kare marar gaskiya, mai ha’inci, sannan ya riƙa neman gafarar Allah, domin shi mai gafara ne, mai yawan rahama ga bayainsa.
Har wa yau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabinsa (ﷺ) kashedi da kada ya zama mai bayar da kariya ga mutanen da suke ha’intar kawunansu, suke aikata laifuka, domin Allah ba ya son masu cin amana, masu laifi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin waɗannan masu laifi cewa, duk sanda za su yi mugun aikinsu, sai su riƙa ɓoye wa mutane don kar a gan su a hana su, amma sun manta ba za su iya ɓoye wa Allah ba, wanda koyaushe yana tare da su da ganinsa da iliminsa a duk inda suke, musamman lokacin da suke haɗuwa tsakar dare, su kwana suna tsara hanyoyin da za su saɓa wa Allah da ayyukan da Allah ba zai yarda da su ba. Sun manta da cewa ilimin Allah yana kewaye da su ta ko’ina.
Sai kuma Allah ya yi wa bayinsa bayanin cewa, idan har sun ba wa waɗannan maciya amana kariya a nan duniya, kariyar kuma ta amfane su ba a yanke musu wani hukunci a kan laifinsu ba, to idan an je lahira a gaban Allah, wane ne suke da shi wanda zai zama wakilinsu, ya kare su daga laifukan da za a tuhume su a kansu?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah yana buɗe ƙofar tuba da gafara ga duk mai zunubin da ya gaggauta tuba da neman gafarar Allah; zai kuma karɓi tubansa, ya yafe masa idan da gaske yake.

2. Saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cutar da kai ne.

3. Haramcin jifan wani da laifin da ba shi ne ya aikata shi ba.

4. Tabbatar da adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), da cewa ba ya kama wani da laifin wani, kamar yadda ba ya yi wa wani uƙubar da ta fi ƙarfin laifinsa.
5. Annabi (ﷺ) shi kansa yana da buƙatar falalar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da rahamarsa, kuma da su ne Allah yake ba shi kariya da tsaro daga duk fitinar wani mai fitina.

6. Wanda duk yake yunƙurin cutar da jama'a, to ya sani ƙarshe ba wanda yake cutarwa sai kansa.

7. Sunnar Annabi (ﷺ) saukakkiya ce daga Allah kamar Alƙur'ani.

8. Falalar koyon ilimi. Domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lissafa shi daga cikin ni'imomin da ya yi wa Annabi (ﷺ).

Suratun Nisa'i (110-113)
وَمَن يَعۡمَلۡ سُوٓءًا أَوۡ يَظۡلِمۡ نَفۡسَهُۥ ثُمَّ يَسۡتَغۡفِرِ ٱللَّهَ يَجِدِ ٱللَّهَ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ١١٠ وَمَن يَكۡسِبۡ إِثۡمٗا فَإِنَّمَا يَكۡسِبُهُۥ عَلَىٰ نَفۡسِهِۦۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ١١١ وَمَن يَكۡسِبۡ خَطِيٓـَٔةً أَوۡ إِثۡمٗا ثُمَّ يَرۡمِ بِهِۦ بَرِيٓـٔٗا فَقَدِ ٱحۡتَمَلَ بُهۡتَٰنٗا وَإِثۡمٗا مُّبِينٗا ١١٢ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكَ وَرَحۡمَتُهُۥ لَهَمَّت طَّآئِفَةٞ مِّنۡهُمۡ أَن يُضِلُّوكَ وَمَا يُضِلُّونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمۡۖ وَمَا يَضُرُّونَكَ مِن شَيۡءٖۚ وَأَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَعَلَّمَكَ مَا لَمۡ تَكُن تَعۡلَمُۚ وَكَانَ فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكَ عَظِيمٗا ١١٣

110. Kuma duk wanda ya aikata mummunan aiki ko ya zalunci kansa, sannan ya nemi gafarar Allah, to zai sami Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.

111. Kuma duk wanda ya aikata wani laifi, to kansa ya yi wa. Kuma Allah Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima.

112. Kuma duk wanda ya aikata wani ƙaramin laifi, ko wani babban zunubi, sannan ya ɗora shi a kan wanda bai ji ba bai gani ba, to haƙiƙa ya ɗaukar wa kansa babban laifin ƙage da kuma wani zunubi mabayyani.

113. Ba don falalar Allah da rahamarsa a kanka ba kuwa, lalle da waɗansu jama'a daga cikinsu sun yi niyyar su ɓatar da kai, ba kuwa kowa za su iya ɓatarwa ba sai dai kawunansu; kuma ba za su cuce ka da komai ba. Kuma Allah Ya saukar maka da Littafi da hikima, kuma Ya sanar da kai abin da a da ba ka sani ba. Kuma falalar Allah mai girma ce gare ka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, duk wanda ya cuci wani ko ya zalunci kansa ta hanyar saɓon Allah, sannan daga baya ya tuba ya nemi gafarar Allah, to Allah zai yafe masa ya ji ƙan sa. Haka kuma duk wanda ya aikata wani laifi, to ya sani kansa ya yi wa, domin uƙubar a kansa za ta ƙare. Allah mai cikakken ilimi ne, ya san wanda ya yi masa laifi da dalilin yin laifin, kuma shi gwani ne mai hikima cikin duk ayyukansa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, duk wanda ya aikata wani laifi babba ko ƙarami, sannan kuma ya ƙaga wa wani wanda bai ji ba, bai gani ba wannan laifin, to haƙiƙa ya shirga mummunar ƙarya, kuma ya ɗauki babban zunubi na wanda ya yi wa ƙagen.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabinsa (ﷺ) cewa, ba don falalar da ya yi masa, da rahamarsa ba, ya tsare shi daga aukawa cikin kowane irin laifi, to da waɗanda suke cin amanar kansu sun yi niyyar kautar da shi daga kan gaskiya, amma kuma ba kowa suke ɓatarwa ba sai kawunanasu. Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya daɗa tuna wa Annabi (ﷺ) ni'imomin da ya yi masa na saukar masa da Alƙur'ani da sunna da koyar da shi sirrikan shari'a, da sauran abubuwan da a da bai sani ba; kuma falalar da Allah ya yi masa mai yawa ce, ba za ta lissafu ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dalilin kasancewar yawancin ganawar mutane alama ce ta rashin gaskiya ko ƙulla wani sharri, shi ne galibi zuciya tana son bayyana aikin alheri a fili, saboda haka duk sa'adda ka ga ana ɓoye-boyen wani al'amari, to yawanci yakan zama ba alheri ba ne.

2. Kada mutum don ya yi aikin alheri ko aikin lada, ya riƙa tunanin lalle sai ya ga sakamakonsa a nan take. Za a iya gaggauto masa sakamakonsa, kuma za a iya jinkirta masa shi zuwa wani lokaci.

3. Haramcin saɓa wa Manzon Allah (ﷺ). Saɓa masa babban zunubi ne da yake jawo uƙubar Allah ga mai aikata shi.

4. Wanda ya ja da wani hukunci na Allah, ko ya saɓa masa a kan rashin sani, to yana da uzuri, har sai hukuncin ya bayyana gare shi. Wanda ya yi sakaci wajen nemam bayanin hukuncin Allah da Manzonsa a kan wani lamari, ya yi aiki da jahilci, to ba shi da wani hanzari a gaban Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Ijma'in malaman wannan al'umma a kan wani hukunci na Musulunci, hujja ce da yake wajaba Musulmi ya bi ta.

6. Dole ne fahimtar maganar Allah da Manzonsa (ﷺ) ta tafi tare da fahimtar magabata na ƙwarai a cikin wannan al'umma, kada ta saɓa tasu.

7. Wajibi ne a kan Musulmi ya yi koyi da Annabi (ﷺ) cikin dukkanin ayyukansa, idan kuwa bai yi ba, to ya kauce wa hanyar Manzon Allah (ﷺ).

8. Kiran wani mahaluƙi da neman agajinsa a kan abin da babu mai yin sa sai Allah, bauta ce ga wanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

9. Duk wani abu da mutum zai yi don canja ƙirar halittar da Allah ya yi masa ta asali don neman kyau da ado wanda shari'a ba ta zo da shi ba, to wannan haramun ne, domin biyayya ce ga Shaiɗan la'ananne.

10. Shigar wa da ɗan'adam burace-burace a zuciyarsa hanya ce ta Shaiɗan don ya halakar da shi.

Suratun Nisa'i (114-122)

*لَّا خَيۡرَ فِي كَثِيرٖ مِّن نَّجۡوَىٰهُمۡ إِلَّا مَنۡ أَمَرَ بِصَدَقَةٍ أَوۡ مَعۡرُوفٍ أَوۡ إِصۡلَٰحِۢ بَيۡنَ ٱلنَّاسِۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ ٱبۡتِغَآءَ مَرۡضَاتِ ٱللَّهِ فَسَوۡفَ نُؤۡتِيهِ أَجۡرًا عَظِيمٗا ١١٤ وَمَن يُشَاقِقِ ٱلرَّسُولَ مِنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُ ٱلۡهُدَىٰ وَيَتَّبِعۡ غَيۡرَ سَبِيلِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ نُوَلِّهِۦ مَا تَوَلَّىٰ وَنُصۡلِهِۦ جَهَنَّمَۖ وَسَآءَتۡ مَصِيرًا ١١٥ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ١١٦ إِن يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ إِنَٰثٗا وَإِن يَدۡعُونَ إِلَّا شَيۡطَٰنٗا مَّرِيدٗا ١١٧ لَّعَنَهُ ٱللَّهُۘ وَقَالَ لَأَتَّخِذَنَّ مِنۡ عِبَادِكَ نَصِيبٗا مَّفۡرُوضٗا ١١٨ وَلَأُضِلَّنَّهُمۡ وَلَأُمَنِّيَنَّهُمۡ وَلَأٓمُرَنَّهُمۡ فَلَيُبَتِّكُنَّ ءَاذَانَ

ٱلۡأَنۡعَٰمِ وَلَأٓمُرَنَّهُمۡ فَلَيُغَيِّرُنَّ خَلۡقَ ٱللَّهِۚ وَمَن يَتَّخِذِ ٱلشَّيۡطَٰنَ وَلِيّٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِ فَقَدۡ خَسِرَ خُسۡرَانٗا مُّبِينٗا ١١٩ يَعِدُهُمۡ وَيُمَنِّيهِمۡۖ وَمَا يَعِدُهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ إِلَّا غُرُورًا ١٢٠ أُوْلَٰٓئِكَ مَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُ وَلَا يَجِدُونَ عَنۡهَا مَحِيصٗا ١٢١ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَنُدۡخِلُهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٗاۚ وَمَنۡ أَصۡدَقُ مِنَ ٱللَّهِ قِيلٗا ١٢٢

114. Babu wani alheri a cikin yawancin ganawarsu, sai fa wanda ya yi umarni da yin sadaka, ko wani aiki nagari ko kuma sulhuntawa tsakanin mutane. Wanda ya aikata haka don neman yardar Allah, to za Mu ba shi lada mai girma.

115. Kuma duk wanda yake saɓa wa wannan Manzo bayan shiriya ta bayyana a gare shi, yake kuma bin tafarkin da ba na muminai ba, to za Mu bar shi da abin da ya ɗaukar wa kansa, sannan Mu shigar da shi wutar Jahannama; makoma kuwa ta munana.

116. Lalle Allah ba Ya gafartawa a yi masa shirka, Yana kuwa gafarta abin da bai kai shirka ba ga wanda Ya ga dama. Duk wanda ya yi wa Allah shirka, to haƙiƙa ya ɓata manisanciyar ɓata.

117. Ba waɗanda suke bauta wa, baya ga Allah, sai wasu gumaka masu sunan mata, kuma babu wanda suke bauta wa sai Shaiɗan mai taurin kai.

118. Allah Ya la’ance shi. Sai kuma ya ce: “Tabbas sai na samu wani kaso ƙayyadajje daga bayinka.

119. “Kuma lalle sai na ɓatar da su, kuma lalle sai na sa musu dogon buri, kuma lalle zan umarce su, sai sun riƙa gutsuttsure kunnuwan dabbobin gida, kuma lalle zan umarce su, sai sun canja halittar Allah.” Duk wanda kuwa ya riƙi Shaiɗan a matsayin masoyi ba Allah ba, to haƙiƙa ya yi hasara bayyananniyar hasara.

120. Yana yi musu alƙawari kuma yana sa musu dogon buri; kuma babu abin da Shaiɗan yake yi musu alƙawari da shi sai ruɗi kawai.

121. Waɗannan makomarsu wutar Jahannama ce, kuma ba za su sami wurin kauce mata ba.

122. Kuma waɗanda suka yi imani, kuma suka yi aiki nagari, za Mu shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu har abada; kuma alƙawarin Allah tabbatacce ne. Kuma wane ne ya fi Allah gaskiyar zance?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara bayyana cewa, duk wani lamari da mutane za su haɗu su keɓe suna tattaunawa a kansa, babu alheri a cikinsa sai in ya danganci umarni da yin sadaka ko kyakkyawan aiki ko sulhu tsakanin mutane. To duk wanda ya aikata waɗannan abubuwa don neman yardar Allah, to Allah zai ba shi gagarumin lada, wanda shi ne gidan Aljanna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kashedi ga duk wanda yake saɓa wa Manzon Allah (ﷺ), ko sunnarsa yana sane, ya yi watsi da gaskiya bayan ta bayyana gare shi, ya zaɓi ya bi wata hanya daban ba hanyar muminai ba, to wannan Allah zai bar shi da mummunan zaɓinsa, ya ɗora masa nauyin da ya ɗaukar wa kansa, makomarsa kuma wutar Jahannama ce, makoma kuwa ta munana.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ƙarara cewa, ba zai taɓa gafarta wa wanda ya mutu yana yi masa shirka bai tuba ba, amma kuma yana gafarta wa wanda ya aikata laifin da bai kai shirka ba idan ya ga dama. Duk ko wanda ya yi shirka, to haƙiƙa ya ɓata manesanciyar ɓata.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani nau'in shirka wanda kafirai suke bauta wa mata, ko dai wasu gumaka masu sunan mata, ko kuma mala'iku, da suka ce wai 'ya'yan Allah ne mata. A gaskiyar lamari dai ba wasu suke bauta wa ba, sai Shaiɗan wanda ya kangare wa Ubangijinsa, wanda kuma Allah ya la'ance shi, ya nisantar da shi daga rahamarsa. Da ma shi Shaiɗan shi ne ya yi rantsuwa gaban Allah cewa lalle, sai ya ɗibi kasonsa daga bayin Allah, ya kautar da su daga kan tafarki madaidaici, ya sa musu yawan burace-burace, wanda hakan shi ne zai nisanta su daga tafarkin Tauhidi da ɗa'a ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Sai kuma ya sa su su riƙa gutsuttsure kunnuwan dabbobinsu, don su nuna wannan alama ce ta `yanta dabbobin cewa an haramta amfani da su wajen hawa ko cin namansu, wai sun zama na gumakansu ne, babu mai taɓa su. Wannan da ma wata al'ada ce da Larabawa suka riƙa yi tun a jahiliyya kafin zuwan Musulunci.
Shaiɗan kuma ya ci gaba da rantsuwar cewa sai ya umarci mutane sun riƙa canja halittar Allah ta asali watau *fiɗra* ta addinin gaskiya, ta hanyar aikata shirka da bidi'a da saɓon Allah sa sunan addini.
Har ila yau canja halittar Allah ya ƙunshi canja wani yanayi na halitta da Allah ya yi musu, kamar ya ƙawata musu yin shasshawa a fuska, ko gyaran gira, ko yin wushirya ta ƙarya wai don ƙarin kyau.
Wannan duk canza halittar Allah ne, wanda galibi mata ne suke yi, wanda kuma bin umarnin Shaiɗan ne, kamar yadda Abdullahi ɗan Mas'ud ya ruwaito. [Dubi, Bukhari #4886, da Muslim #2125].
Duk kuma wanda ya riƙi Shaiɗan masoyi, yana yi masa biyayya, to haƙiƙa ya halaka, duniya da lahira. Da ma shi Shaiɗan alƙawarin ƙarya yake yi wa mabiyansa, yana ruɗar su don ya halakar da su. Yakan yi musu alƙawarin zai taimaka musu, ko ya tsorata su da cewa, idan suna ciyar da dukiyarsu don Allah za su talauce, kuma ya dinga sa musu burin cewa in sun bi hanyarsa za su sami ɗaukaka ta duniya. To waɗanda suka riƙi Shaiɗan a matsayin masoyinsu, mai jiɓintar al'amuransu, makomarsu wutar Jahannama ce mai tsananin ƙuna, kuma ba za su taɓa samun mafaka ko wurin tsira ba daga gare ta.
To amma waɗanda suka yi imani, suka yi ayyuka na ƙwarai, waɗannan 'yan Aljanna ne, za su shige ta su dawwama a cikinta. Wannan shi ne alƙawarin Allah na gaskiya kuma babu wanda maganarsa ta fi zama gaskiya kamar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rushe dogaro a kan duk wani buri, ya tabbatar da cewa, aikin ƙwarai shi kaɗai ne zai tseratar da bawa daga azabar Allah.

2. Duk wani aiki mai kyau ba zai sami karɓuwa ba a wurin Allah, sai mai shi ya gina shi a kan harsashi na imani. Aikin da ya rasa harsashi na imani tamkar bishiya ce da aka sare duk saiwoyinta, ko kuma gini a kan kumfar teku.

3. Duk wani azzalumi zai gamu da sakamakon zaluncinsa babu makawa, kada ya ruɗu da ƙoshin lafiyarsa ko dukiyarsa ya yi zaton ya tsira; wannan wani ɗan jin daɗi ne na ƙanƙanin lokaci kafin lokacin uƙubarsa ya zo.

4. Ibada ba za ta zama karɓaɓɓiya ba a wurin Allah, sai ta zama ta ƙwarai. Alamar zamanta ta ƙwarai shi ne ta dace da koyarwar shari'a.

5. Ibada ba za ta karɓu ba a wurin Allah, sai mai yin ta ya zama mai ikhlasi, wato ya yi ta domin Allah kaɗai.

Suratun Nisa’i (123-126)

لَّيْسَ بِأَمَانِيِّكُمْ وَلَآ أَمَانِيِّ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ ۗ مَن يَعْمَلْ سُوٓءًا يُجْزَ بِهِۦ وَلَا يَجِدْ لَهُۥ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلِيًّا وَلَا نَصِيرًا ﴿١٢٣﴾ وَمَن يَعْمَلْ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِن ذَكَرٍ أَوْ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَأُو۟لَٰٓئِكَ يَدْخُلُونَ ٱلْجَنَّةَ وَلَا يُظْلَمُونَ نَقِيرًا ﴿١٢٤﴾ وَمَنْ أَحْسَنُ دِينًا مِّمَّنْ أَسْلَمَ وَجْهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحْسِنٌ وَٱتَّبَعَ مِلَّةَ إِبْرَٰهِيمَ حَنِيفًا ۗ وَٱتَّخَذَ ٱللَّهُ إِبْرَٰهِيمَ خَلِيلًا ﴿١٢٥﴾ وَلِلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ مُّحِيطًا ﴿١٢٦﴾

123. (Al’amarin) ba wai ya dangaci burace-buracenku ba ne, ba kuma burace-buracen Ma’abota Littafi ba ne. Duk wanda ya aikata mummunan aiki, to za a saka masa da shi, kuma ba zai sami wani masoyi ko mai taimako ba Allah ba.
124. Kuma wanda ya yi wani aiki nagari, namiji ne ko mace, alhali yana mumini, to waɗannan za su shiga Aljanna, kuma ba za a zalunce su gwargwadon ɗigon bayan ƙwallon dabino ba.

125. Kuma wane ne mafi kyawun addini fiye da wanda ya miƙa fuskarsa ga Allah, yana kuma mai kaɗaita Allah, sannan ya bi addinin Ibrahimu yana mai karkacewa duk wata ɓarna? Allah kuwa Ya riƙi Ibrahimu a matsayin badaɗayi.

126. Kuma abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa duk na Allah ne. Kuma Allah Ya kasance Yana kewaye da (sanin) komai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana shaida wa Musulmi da Yahudawa da Nasara cewa, samun tsira a ranar lahira ba yana samuwa ne ta hanyar burace-burace ba, ba tare da wani aiki ba. A cikinsu duk wanda ya yi wani mummunan aiki babba ko ƙarami, za a yi masa sakayya a kansa a duniya ko a lahira, kuma ba zai taɓa samun wani mai taimaka masa ya ba shi kariya in ba Allah ba. Wanda kuma ya yi kyakkyawan aiki, namiji ne shi ko mace, alhali yana mai imani da Allah da Manzonsa (ﷺ), to waɗannan su ne za su shiga Aljanna gidan ni’ima ba tare da an zalunce da su komai ba; za a ba su ladansu cikakke kamar yadda aka yi musu alƙawari.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, babu mutumin da addininsa ya fi kyau kamar wanda ya miƙa wuyansa ga Allah shi kaɗai, kuma ya bi shari’a sau-da-ƙafa, kuma ya bi addinin Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) mai kauce wa duk wata shirka kuma addini na Tauhidi. Allah kuma ya bayyana girman matsayin Annabi Ibrahim a wurinsa, yayin da ya riƙe shi badaɗayi, wanda yake muƙami ne na ƙoli da Allah yake ba wa masoyansa, muƙami na ƙololuwar soyayyar Allah ga bawansa, a dalilin yadda shi ma wannan bawan ya tsantsanta bautarsa da soyayyarsa ta ƙoli ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikakken ikonsa a kan komai. Domin duk abin da yake cikin sammai da wanda yake ƙasa nasa ne, mulkinsa ne, bayinsa ne, shi ne yake yin yadda ya ga dama da su, kuma iliminsa ya game ko’ina.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗayin sahabbai wajen neman ilimin abin da ba su sani ba na hukunce-hukuncen shari’a.

2. Yadda sahabbai suka ɗauki sha’anin mata da muhimmanci.

3. Himmatuwa da kula da sha’anin mata da marayu, musamman marainiya, saboda ita rauni biyu ta haɗa, raunin maraici da kuma raunin kasancewarta mace.

4. Bayanin zaluncin Larabawa a zamanin jahiliyya da rashin tausayinsu ga mata da yara marayu.

5. Muhimmancin kula da haƙƙoƙin masu rauni cikin al’umma.

Suratun Nisa’i (127)

وَيَسْتَفْتُونَكَ فِي ٱلنِّسَآءِۖ قُلِ ٱللَّهُ يُفْتِيكُمْ فِيهِنَّ وَمَا يُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ فِي ٱلْكِتَٰبِ فِي يَتَٰمَى ٱلنِّسَآءِ ٱلَّٰتِي لَا تُؤْتُونَهُنَّ مَا كُتِبَ لَهُنَّ وَتَرْغَبُونَ أَن تَنكِحُوهُنَّ وَٱلْمُسْتَضْعَفِينَ مِنَ ٱلْوِلْدَٰنِ وَأَن تَقُومُواْ لِلْيَتَٰمَىٰ بِٱلْقِسْطِۚ وَمَا تَفْعَلُواْ مِنْ خَيْرٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِهِۦ عَلِيمًا ١٢٧

127. Kuma suna neman fatawarka game da lamarin mata. Ka ce: “Allah ne Yake ba ku fatawa game da lamarinsu da kuma abin da ake karanta muku a cikin Littafi dangane da marayu mata waɗanda ba kwa iya ba su sadakinsu cikakke, ga shi kuma kuna kwaɗayin ku aure su; hakanan da kuma (dukiyar) yara masu rauni. Kuma ku tsaya wajen kula da (dukiyar) marayu ta hanyar adalci. Kuma duk abin da kuka aikata na alheri, to lalle Allah Yana sane da shi.”

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, sahabbansa suna neman fatawarsa game da lamarin mata. Allah ya ce da shi ya faɗa musu cewa, shi ne zai ba su amsar fatawarsu game da hukunce-hukuncen mata, kuma zai ba su wannan fatawar ne da Alƙur’anin da ake karanta musu dangane da sha’anin mata marayu da suke ƙarƙashinsu, suna kula da su bayan mutuwar iyayensu; sai su riƙa zaluntar su ta ɗaya daga cikin waɗannan hanyoyi:

• Su hana su gadonsu ko;
• su hana su yin aure don su ci gaba da morar kuɗaɗensu ko;
• su ƙwace musu sadakinsu da aka ba su lokacin aurensu.

Wannan idan su ba sa sha’awar su aure su saboda su ba kyawawa ba ne. Amma idan sun gan su kyawawa ne masu dukiya, to sai su aure su, amma su hana su sadakinsu cikakke. To Allah ya haramta musu yin wannan.

Haka kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba su fatawa dangane da yara ƙanana raunana da cewa, su ba su haƙƙoƙinsu na gado, kada su cinye musu gadonsu bisa ga zalunci. Sannan su yi cikakken adalci ga marayu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, yana sane da duk wanda ya aikata wani alheri, kuma zai ba shi cikakken sakamakonsa.

An karɓo daga Urwatu ɗan Zubairu, ya tambayi A’isha (Allah ya kara mata yarda) game da faɗar Allah: “Kuma idan kuna jin tsoron cewa ba za ku iya yin adalci ba dangane da marayu, to ku auri matan da kuke so, ko dai biyu-biyu ko uku-uku ko huɗu-huɗu.” Sai ta ce: “Ya kai ɗan ‘yar’uwata, ana magana ne a kan marainiya da take wurin mai kula da ita (waliyyinta), tana tarayya da shi a dukiyarsa, sai ya yi sha’awar dukiyarta da kuma kyawunta, sai ya so ya aure ta amma ba tare da ya yi mata adalci wajen ba ta sadakinta ba, ya ba ta abin da idan wani ne zai aure ta ba shi zai ba ta ba. Sai aka hana musu auren su, sai fa idan za su yi musu adalci wajen biyan su sadakin da ya dace da a ba su a al’ada. Wannan ya sa aka umarce su da su auri wasu matan daban waɗanda suke so.” Urwatu ya ce: A’isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: “Sannan sahabbai suka nemi fatawa daga Manzon Allah game da su bayan wannan ayar, sai Allah ya saukar da faɗinsa: “Kuma suna tambayar ka dagane da lamarin mata…” Ta ce: “Ayar da Allah ya ambata cewa ana karanta musu ita a littafi ita ce waccan ayar ta farko.” [Bukhari #2494, da Muslim #3018].

Daga wannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutum ya haƙura ya bar wani haƙƙinsa ga ɗan’uwansa abu ne mai nauyi, to amma idan ya yi la’akari da amfanin da ke cikin yin sulhu, aikata shi yakan yi masa sauƙi.

2. Kira zuwa ga kyautata wa mata wajen mu’amalar zamantakewar aure, ko da kuwa akwai wani abu na ƙiyayya a zuciya gare su ko rashin sha’awar su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da yin taƙawa domin kada ƙiyayya ta sanya miji ya cutar da matarsa.

3. Gyara da kuma tsoron Allah abubuwa ne masu janyo gafarar Allah ga bawa.

4. Toshe ƙofar fitar da rai daga samun rahamar Allah, domin falalar Allah mayalwaciya ce.

5. Sulhu alheri ne. Tana yiwuwa wani ya yi zaton cewa idan ya haƙura da wani haƙƙi nasa, kamar ya zama wani sakarai, wanda bai san ciwon kansa ba, kuma nan gaba zai yi da-na-sani; to sai Allah mai kowa, mai komai ya shaida masa cewa: “Sulhu alheri ne.”

Suratun Nisa’i (128-130)
وَإِنِ ٱمۡرَأَةٌ خَافَتۡ مِنۢ بَعۡلِهَا نُشُوزًا أَوۡ إِعۡرَاضٗا فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡهِمَآ أَن يُصۡلِحَا بَيۡنَهُمَا صُلۡحٗاۚ وَٱلصُّلۡحُ خَيۡرٞۗ وَأُحۡضِرَتِ ٱلۡأَنفُسُ ٱلشُّحَّۚ وَإِن تُحۡسِنُواْ وَتَتَّقُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٗا ١٢٨ وَلَن تَسۡتَطِيعُوٓاْ أَن تَعۡدِلُواْ بَيۡنَ ٱلنِّسَآءِ وَلَوۡ حَرَصۡتُمۡۖ فَلَا تَمِيلُواْ كُلَّ ٱلۡمَيۡلِ فَتَذَرُوهَا كَٱلۡمُعَلَّقَةِۚ وَإِن تُصۡلِحُواْ وَتَتَّقُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ١٢٩ وَإِن يَتَفَرَّقَا يُغۡنِ ٱللَّهُ كُلّٗا مِّن سَعَتِهِۦۚ وَكَانَ ٱللَّهُ وَٰسِعًا حَكِيمٗا ١٣٠

128. Kuma idan wata mace ta ji tsoron burtsewa daga mijinta, ko bijirewa, to babu laifi su yi sulhu a tsakaninsu. Kuma yin sulhu shi ya fi alheri. Kuma an kimsa wa rayuka tsananin rowa. Idan kuka kyautata, kuma kuka yi taƙawa, to lalle Allah Ya kasance Masanin abin da kuke aikatawa ne.

129. Kuma ba za ku iya yin adalci (na soyayya) a tsakankanin mata ba, ko da kuna matuƙar son yin hakan. To kada ku karkata, karkata ta gaba ɗaya, ta yadda za ku ƙyale ɗayar kamar ratayayya. Amma idan za ku kyautata kuma ku yi taƙawa, to lalle Allah Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.

130. Idan kuwa suka rabu, to Allah zai wadatar da kowannensu daga yalwarsa. Kuma Allah Ya kasance Mayalwaci ne, Mai yawan hikima.

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin wasu hukunce-hukuncen da suka shafi ma’aurata ne yayin da aka sami saɓani a tsakaninsu. Idan mace ta lura mijinta ya fara gajiya da ita, ko yana ja baya-baya da ita, saboda yawan shekarunta, to tana iya neman sa da sulhu, babu laifi ta sarayar da wani haƙƙinta, kamar na kwana ko ciyarwa ko tufatarwa, domin su ci gaba da zama da mijinta a matsayin ma’aurata, domin yin haka ya fi musu alheri fiye da su rabu gaba ɗaya. To sai dai kuma yin hakan wani abu ne mai wuyar gaske saboda yadda aka sanya wa zukata tsananin ƙanƙame abin da yake haƙƙi ne gare su. Sai dai yana da kyau mutum ya yi ƙoƙari ya danne zuciyarsa, ya haƙura da wani abu na haƙƙinsa domin a sami daidaito ta yin sulhu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar a kan kyautatawa ta kowane ɓangare; ta ɓangaren ibada da ta ɓangaren mu’amala da ta ɓangaren zamantakewar aure da kyautata wa mata ko da kuwa mazajensu sun fara gajiya da su, sai su yi haƙuri, su ba su haƙƙinsu cikakke, kuma su kiyaye dokokin Allah game da su. Idan sun yi haka, to su sani Allah yana da cikakken sanin duk abin da suke aikatawa, kuma zai musu sakayya a kai.

An karɓo daga A’isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: “Wannan ayar tana magana ne game da mutumin da yake tare da matarsa, amma ba ya son ci gaba da zama da ita, ya fara tunanin ya sake ta, sai ita kuma

matar ta ce masa: “Ka ƙyale ni na ɗauke maka duk wata ɗawainiyata.” Sai Allah ya saukar da wannan ayar.” [Bukhari #2450, da Muslim #3021].

A’isha (Allah ya kara mata yarda) kuma ta ruwaito cewa, Saudatu ‘yar Zam’ah lokacin da ta ga ta fara manyanta, ta ji tsoron ko Annabi (ﷺ) zai sawwaƙe mata, sai ta ce da shi: “Ya Manzon Allah (ﷺ), na ba wa A’isha kwanana, sai ko Annabi (ﷺ) ya karɓi wannan kyautar daga gare ta. A’isha ta ce: “Muna ganin a kanta ne da ire-irenta wannan ayar ta sauka.” [Abu Dawud #2135, da Al-Hakim #2760].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da cewa, duk yadda maza suka yi ƙoƙarin tabbatar da adalci a tsakanin matansu, ba za su iya ba, dole ne a sami fifikon soyayyar zukata dangane da su. To amma fa ba a yarda su karkata gaba ɗaya ga ɗayar su ƙyale ɗayar a rataye, ita ba a sake ta ba, ita kuma ba mai aure ba. Allah kuma ya ƙara jaddada batun sulhu da fahimtar juna tsakanin ma’aurata da kuma tsoron Allah cikin lamarin aure. Allah ya ce in sun yi haka, to shi mai gafara ne, mai jin ƙai. Idan kuma abu ya ci tura, sulhu ya ki yiwuwa, har an kai ga saki, to Allah zai haɗa kowa da rabonsa, domin falalar Allah tana da yalwa, ba ta da iyaka, kuma shi gwani ne, mai hikima cikin duk hukunce-hukuncensa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin taƙawa, shi ya sa Allah ya yi wa mutanen farko da na ƙarshe wasiyya da ita.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa wannan al’umma ta Musulmi cewa, ya yi wa al’ummomin da suka gabace su wasiyya da taƙawa, domin ya zaburar da su wajen lazimtar ta, don kada waɗancan al’ummomin sun tsere musu.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba yana umartar mutane da taƙawa ba ne domin yana da wata buƙata a wajensu; yana yin haka ne domin amfaninsu su kansu da gyaran zukatansu.

4. Idan mumini ya tashi roƙon Allah, to ya roƙe shi duniya da lahira, domin duk a hannunsa suke, kuma samun lahirar shi ne mafi alfanu ga ɗan’adam.

5. Allah ne shi kaɗai mai bayar da sakamakon duniya da na lahira, don haka a wurinsa ya wajaba a nema.

Suratun Nisa’i (131-134)

وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَلَقَدۡ وَصَّيۡنَا ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِكُمۡ وَإِيَّاكُمۡ أَنِ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ وَإِن تَكۡفُرُواْ فَإِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَنِيًّا حَمِيدٗا ١٣١ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا ١٣٢ إِن يَشَأۡ يُذۡهِبۡكُمۡ أَيُّهَا ٱلنَّاسُ وَيَأۡتِ بِـَٔاخَرِينَۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ ذَٰلِكَ قَدِيرٗا ١٣٣ مَّن كَانَ يُرِيدُ ثَوَابَ ٱلدُّنۡيَا فَعِندَ ٱللَّهِ ثَوَابُ ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ سَمِيعَۢا بَصِيرٗا ١٣٤

131. Kuma duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa na Allah ne. Kuma haƙiƙa Mun yi wasiyya ga waɗanda Muka bai wa Littafi gabaninku da ku kanku cewa, ku ji tsoron Allah. Idan kuwa kuka kafirce, to lalle abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa duka na Allah ne. Kuma Allah Ya kasance Mawadaci ne, Sha-yabo.

132. Kuma duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa na Allah ne. kuma Allah Ya isa Abin dogaro.

133. Idan Ya ga dama sai Ya tafiyar da ku, ya ku mutane, kuma Ya kawo waɗansu daban. Allah kuwa Ya kasance Mai iko ne a kan hakan.

134. Duk wanda ya kasance yana son ladan duniya, to ladan duniya da na lahira duk a hannun Allah suke. Kuma Allah Ya kasance Mai ji ne, Mai gani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, shi kaɗai yake da mulkin abin da yake sammai da abin da yake ƙasa; shi ne mai sarrafa su yadda ya ga dama. Kuma haƙiƙa ya yi wa Yahudawa da Nasara wasiyya, har ma da Musulmi cewa, su kiyaye dokokin Allah, ta hanyar aikata umarninsa da guje wa haninsa. Idan kuwa suka kafirce masa, to ba za su cuce shi da komai ba, sai dai su cuci kawunansu, domin wannan ba zai tauye komai cikin mulkinsa ba. Duk abin da yake cikin sammai da na cikin ƙasa mulkinsa ne, kowa mai buƙata ne a wajensa, amma shi ba shi da buƙatar komai a wajen kowa; yana da siffofi na kamala, kuma shi ne sha-yabo a kan ni'imominsa da kyautatawarsa ga bayinsa. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ga dama duk sai ya halaka mutane gaba ɗaya, ya kawo wasu daban waɗanda suka fi tsoronSa da yi masa ɗa'a. Allah kuma yana da cikakken iko a kan yin hakan. Don haka duk wanda yake duniya ce a ransa, ba ya tunanin sakamakon lahira, to ya sani fa cewa sakamakon duniya da na lahira duka a hannun Allah suke, kuma yana ba da su ga duk wanda ya nema. Shi kuma wancan mai neman duniya kaɗai, me zai hana shi ya nemi duka biyun? Lalle Allah yana jin kowa, yana kuma ganin komai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsayuwa da adalci yana daga cikin manyan al'amura masu nuna addinin mutum da riƙonsa ga Musulunci.

2. Yin ikhlasi yayin bayar da shaida.

3. Haramcin bin son zuciya har a kai ga rashin gaskiya.

4. Mutum ya guji canje-canjen sheƙa, yau yana tare da wannan ra'ayi, gobe ya canja ya kama wani, jibi ya sake sheƙa zuwa ga wani ra'ayin daban. Abin da yake wabiji a kansa shi ne neman gaskiya, duk sa'adda ya riske ta, to ya ƙanƙame ta sosai har zuwa mutuwarsa.

5. Wajibi ne yin adalci wajen ba da shaida, ba tare da ƙari ko ragi ba, kuma kada mutum ya ƙi ba da ita idan an buƙace shi da ya bayar.

6. Wajabcin karɓar shaidar ɗa a kan laifin iyayensa ko danginsa.

7. Kafirci yana ƙaruwa kuma yana raguwa, kamar yadda imani yake ƙaruwa yake raguwa.

Suratun Nisa'i (135-137)

۞يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ بِٱلۡقِسۡطِ شُهَدَآءَ لِلَّهِ وَلَوۡ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمۡ أَوِ ٱلۡوَٰلِدَيۡنِ وَٱلۡأَقۡرَبِينَۚ إِن يَكُنۡ غَنِيًّا أَوۡ فَقِيرٗا فَٱللَّهُ أَوۡلَىٰ بِهِمَاۖ فَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلۡهَوَىٰٓ أَن تَعۡدِلُواْۚ وَإِن تَلۡوُۥٓاْ أَوۡ تُعۡرِضُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٗا ١٣٥ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِي نَزَّلَ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ مِن قَبۡلُۚ وَمَن يَكۡفُرۡ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ١٣٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ثُمَّ كَفَرُواْ ثُمَّ ءَامَنُواْ ثُمَّ كَفَرُواْ ثُمَّ ٱزۡدَادُواْ كُفۡرٗا لَّمۡ يَكُنِ ٱللَّهُ لِيَغۡفِرَ لَهُمۡ وَلَا لِيَهۡدِيَهُمۡ سَبِيلَۢا ١٣٧

135. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku zamo masu tsayawa da adalci, kuna masu ba da shaida don Allah, ko da kuwa a kan kawunanku ne ko a kan mahaifanku ko a kan dangi makusanta. Idan ya kasance mawadaci ne ko matalauci, to Allah Shi ne Ya fi sanin abin da ya fi cancanta gare su; don haka kada ku bi son zuciyarku ku ƙi yin adalci. Idan kuwa kuka karkatar da shaida ko kuka ƙi ba da ita, to lalle Allah Ya kasance Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne.

136. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi imani da Allah da Manzonsa da Littafin da Ya saukar ga Manzonsa da Littafin da Ya saukar gabaninsa. Duk wanda kuwa ya kafirce wa Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa da ranar ƙarshe, to haƙiƙa ya ɓace ɓata mai nisa.
137. Lalle waɗanda suka yi imani, sannan daga baya suka kafirce, sannan kuma suka ƙara yin imani, sannan suka kafirce, sannan suka ƙara kafirci, waɗannan Allah ba zai yi musu gafara ba, ba kuma zai shiryar da su tafarki madaidaici ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar bayinsa da su zama masu adalci dangane da haƙƙoƙin Allah da na bayinsa, su bayar da shaida don Allah, ko da kuwa shaidar su kansu ta shafa ko iyayensu ko danginsu. Kada su yi la'akari da cewa wane mawadaci ne, bari su daɗaɗa masa, ko wane matalauci ne, bari su tausaya masa. Lalle su fahimta cewa da mai wadata da matalauci duk al'amurransu na ga Allah, ya fi kowa sanin abin da ya fi zama maslaha a gare su, don haka kada su bi son zuciya su ƙi yin adalci. Idan suka karkatar da shaida ko suka ƙi bayar da ita, to su sani cewa Allah yana da cikakkiyar masaniya game da abin da suke aikatawa kuma zai saka wa kowa a kan abin da ya aikata.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su tsaya ƙyam a kan imaninsu da Allah da Annabinsa (ﷺ), su riƙe addininsu, kuma su yi imani da Alƙur'ani da littattafan da suka gabata, waɗanda Allah ya saukar. Duk kuwa wanda ya kafirce wa Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa da ranar lahira, to haƙiƙa ya ɓata daga hanya madaidaiciya mummunar ɓacewa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk mutumin da ya ce shi mumini ne ya kafirta, bayan nan sannan ya sake dawowa mumini, sai kuma ya sake kafirta, ya ci gaba da kafircinsa, to wannan Allah ba zai taɓa gafarta masa ba, kuma ba zai yi masa katari na dacewa da bin tafarkin gaskiya ba, domin ya zaɓa wa kansa ɓata da kafirci a kan shiriya da imani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ya kamata ga mumini ya cire kwaɗayin samun girma daga kowa in ba Allah ba, ya nemi ɗaukaka da matsayi a wurin Allah shi kaɗai.

2. Mutanen da suke tutiya da iyayensu kafirai, ko suke alfahari da asalinsu na maguzanci su ne masu neman ɗaukaka daga wajen kafirai. Wannan yana daga cikin neman ɗaukaka daga wajen kafirai.

3. Wanda duk ya zauna tare da masu saɓon Allah, ba don ya hana su aikata laifinsu ba, to shi ma ɗaya yake da su, laifin da aka rubuta musu irinsa za a rubuta masa.

4. Kamar yadda idan mutum ya zauna cikin masu saɓon Allah ake rubuta masa zunubi, to hakanan shi ma wanda ya zauna tare da mutanen kirki yayin da suke ayyukan alheri, shi ma zai sami ladan zama cikinsu.

5. Yayin da munafukai suka riƙi kafirai masoya a duniya, sai Allah ya haɗa su wuri guda a lahira. To haka kowane mutum yake tare da wanda yake so.

6. Musulmi ya guji halayya irin ta munafuƙai lokacin tashi ya yi salla. Ya tashi cikin nishaɗi da walwala ya yi sallarsa, kuma cikin nutsuwa da halarto zuciyarsa ga Ubangijinsa.

7. Wanda duk ya yi wani aiki domin riya, to ya kwaikwayi halin munafuƙai, don haka ya yi kama da su.

8. Yana da kyau Musulmi ya zamanto koyaushe mai nutsuwa ne da kimtsi a cikin dukkan lamuransa, ba mai tsalle-tsalle ba, yau yana nan gobe yana can, yana bibiyar soye-soyen zuciyarsa.

9. Komawa zuwa ga Allah da neman shiriya a wurinsa.

Suratun Nisa'i (138-143)

بَشِّرِ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ بِأَنَّ لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمًا ١٣٨ ٱلَّذِينَ يَتَّخِذُونَ ٱلۡكَٰفِرِينَ أَوۡلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۚ أَيَبۡتَغُونَ عِندَهُمُ ٱلۡعِزَّةَ فَإِنَّ ٱلۡعِزَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًا ١٣٩
وَقَدۡ نَزَّلَ عَلَيۡكُمۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ أَنۡ إِذَا سَمِعۡتُمۡ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ يُكۡفَرُ بِهَا وَيُسۡتَهۡزَأُ بِهَا فَلَا تَقۡعُدُواْ مَعَهُمۡ حَتَّىٰ يَخُوضُواْ فِي حَدِيثٍ غَيۡرِهِۦٓۚ إِنَّكُمۡ
إِذٗا مِّثۡلُهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ جَامِعُ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱلۡكَٰفِرِينَ فِي جَهَنَّمَ جَمِيعًا ١٤٠ ٱلَّذِينَ يَتَرَبَّصُونَ بِكُمۡ فَإِن كَانَ لَكُمۡ فَتۡحٞ مِّنَ ٱللَّهِ قَالُوٓاْ أَلَمۡ نَكُن
مَّعَكُمۡ وَإِن كَانَ لِلۡكَٰفِرِينَ نَصِيبٞ قَالُوٓاْ أَلَمۡ نَسۡتَحۡوِذۡ عَلَيۡكُمۡ وَنَمۡنَعۡكُم مِّنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۚ فَٱللَّهُ يَحۡكُمُ بَيۡنَكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ وَلَن يَجۡعَلَ
ٱللَّهُ لِلۡكَٰفِرِينَ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ سَبِيلًا ١٤١ إِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ يُخَٰدِعُونَ ٱللَّهَ وَهُوَ خَٰدِعُهُمۡ وَإِذَا قَامُوٓاْ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ قَامُواْ كُسَالَىٰ يُرَآءُونَ ٱلنَّاسَ وَلَا
يَذۡكُرُونَ ٱللَّهَ إِلَّا قَلِيلٗا ١٤٢ مُّذَبۡذَبِينَ بَيۡنَ ذَٰلِكَ لَآ إِلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِ وَلَآ إِلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِۚ وَمَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ سَبِيلٗا ١٤٣

138. Ka yi albishir ga munafuƙai cewa, suna da wata azaba mai raɗaɗi.

139. Su ne waɗanda suke riƙar kafirai a matsayin masoya, su ƙyale muminai. Shin suna neman wata ɗaukaka ce a wurinsu? To lalle ɗaukaka gaba ɗaya ta Allah ce.

140. Kuma haƙiƙa Ya saukar muku a cikin littafi cewa, idan kuka ji ayoyin Allah ana kafirce musu, ana izgili da su, to kar ku zauna tare da su har sai sun shiga cikin wani zancen daban ba wannan ba. Lalle in har kuka zauna tare da su, to kun zama kamarsu. Lalle Allah Mai tattara munafuƙai ne da kafirai cikin wutar Jahannama gaba ɗaya.

141. Su ne waɗanda suke fakon ku, idan kun sami wata nasara daga Allah sai su ce: "Shin ashe ba tare da ku muke ba?" Kuma idan kafirai ne suka samu wata nasara, sai su ce: "Ashe ba mu muka sami dama a kanku ba (amma muka ƙyale ku), kuma muka kare ku daga muminai?" To lalle Allah zai yi hukunci a tsakaninku ranar alƙiyama, kuma Allah ba zai taɓa ba wa kafirai wata dama ba a kan muminai.

142. Lalle munafuƙai suna yaudarar Allah, alhali kuwa Shi Mai mayar musu da sakamakon yaudararsu ne; kuma idan sun tashi zuwa salla, za su tashi suna masu kasala ne, suna yin aiki don mutane su gani, kuma ba su ambaton Allah sai kaɗan.

143. Suna ta kai-kawo tsakanin haka (kafirci da imani), su ba sa tare da waɗanan, kuma ba sa tare da waɗancan. Duk wanda Allah Ya ɓatar da shi kuwa, to babu yadda za ka iya sama masa wani tafarki na shiriya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana halayen munafuƙai ne na rashin gaskiya da ƙin yin imani da Allah da Manzonsa (ﷺ). A fili suna nuna su Musulmi ne, amma a ɓoye suna tare da kafirci da kafirai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi da ya yi musu albishir da wata azaba

mai raɗaɗi, domin sun nuna ƙauna da goyon baya ga kafirai maimakon muminai. Wai me ya sa suke aikata hakan? Shin wani girma suke nema a wajen kafirai? To ai kuwa ba za su same shi ba, domin girma gaba ɗaya na Allah ne shi kaɗai, shi yake bayar da shi, kuma ga muminai kaɗai yake ba da shi, don haka munafuƙai ba za su same shi ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa, ya zartar da hukunci a Alƙur'ani na cewa, idan suka ji ana yin izgili da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ana kafirce musu, to kada su kuskura su zauna tare da masu izgilin har sai sun bari, sun shiga wata tattaunawar daban wadda ba ta izgili ba. Idan kuwa har suka yarda suka zauna tare da su cikin wannan hali na izgili da kafirce wa ayoyin Allah, to su ma sun zama kamar su, sun yi tarayya da su a cikin laifi. A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ishara ne zuwa ga aya ta 68 cikin Suratul An'am, wadda ta haramta wa muminai zama inda ake yi wa shari'ar Allah izgili da rashin kunya.
Waɗannan munafuƙan su ne koyaushe suke sa ido su ga abin da zai faru ga muminai, mai kyau ko marar kyau. Idan suka ga Allah ya ba wa muminai nasara a kan kafirai a wajen yaƙi, sun fatattaki kafirai, sun kwashi ganima, sai ka ji su suna ce wa muminai: "Shin ba tare da ku muke ba, kuma tare muka fita yaƙin?" Suna neman a ba su kasonsu daga ganimar. Idan kuwa kafirai ne suka sami nasara a kan muminai, har suka kwashe dukiyoyin muminai, to a nan ma sai ka ji munafuƙai suna ce wa kafirai: "Yanzu ashe ba mun taimaka muku ba, mun ba ku tsaro daga muminai?" Suna son a nan ma kafirai su yaga musu wani kaso daga dukiyar da suka samu ta muminai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ranar alƙiyama zai yi hukunci tsakanin muminai da kafirai, ya shigar da muminai gidajen Aljanna, ya shigar da kafirai da munafuƙai wutar Jahannama. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin cewa ba zai taɓa ba wa kafirai nasara a kan muminai gaba ɗaya ba. Wato suna iya samun nasara a kansu a wani wuri ban da wani wuri. Hakanan ba zai taɓa ba wa kafirai wata hujja ba wadda za su rinjayi muminai da ita a ranar lahira.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fallasa wani mummunan tunani na munafuƙai da yaudara ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Wato su tunda sun bayyana Musuluncinsu a fili don su samu kare rayukansu da dukiyoyinsu, a nan duniya, kuma har ma suna tunanin wannan dabarar za ta amfane su har a lahira, amma ba su san da cewa Allah ya fi su iya mayar da martanin yaudararsu ba, ya hana a kashe su ko a taɓa dukiyoyinsu a nan duniya, amma ya yi musu talala har su iske shi ranar lahira, ya kama su da laifinsu, ya shigar da su wutar Jahannama. Tir da wannan makoma.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan munafuƙai da ma ba addini suka damu da shi ba; duk sa'adda suka tashi salla, sukan yi ta ne cikin kasala da mutuwar jiki, domin a bisa dole ne suke yin ta don muminai su gan su suna salla, su yarda cewa, su ma suna tare da su, ba sa kuma ambaton Allah da harsunansu da gaɓoɓinsu da zukatansu cikin sallarsu, ba sa sanin ma abin da suke faɗa saboda zukatansu sun cika da gafala da riya da munafunci.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Na ji Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wannan ita ce sallar munafuki. Yakan zauna ya zuba wa rana ido har sai ta kasance tsakanin ƙahonnin Shaiɗan biyu (wato ta tafi faɗuwa), sai ya miƙe tsaye ya duddungura raka'a huɗu, ba ya ambaton Allah a ciki sai ɗan kaɗan." [Muslim #22].

Har wa yau waɗannan munafukan mutane ne masu kai-kawo tsakanin imani da kafirci. Su ba su tare da muminai gaba ɗayansu, kuma ba sa tare da kafirai gaba ɗayansu; a fili suna tare da muminai, a ɓoye kuma suna tare da kafirai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Misalin munafuki kamar misalin akuya ce mai kai-komo tsakanin dabbobi, wani lokaci ta kaɗa ta shiga waɗannan, wani lokaci kuma ta kaɗa ta koma wajen waɗancan." [Muslim #2784].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya ɓatar daga kan hanyar shiriya saboda laifukansa, to ba za ka taɓa sama masa wata hanyar shiriya ba har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya yi ɓarna, to ba za a karɓi tubansa ba, sai ya dawo ya gyara abin da ya ɓata.

2. Wanda duk ya riƙi wani ba Allah ba, to sharaɗin karɓar tubansa shi ne ya saki wannan abu ya dawo ya riƙe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sannan tubansa zai inganta.
3. Ikhlasi yana daga cikin sharuɗɗan karɓar tuban mushiriki da munafuƙi, domin ayyukansu tattare suke da shirka da Allah da riya.

4. Kwaɗaitarwa a kan godiya ga Allah da girman matsayinta a wurin Allah, duba da yadda ya haɗa godiya da imani wuri guda.

5. Wanda bai yi imani da Allah ya gode masa ba, zai fuskanci azabarsa.

6. Allah Sarki ne mai cikakken adalci; ba ya azabtar da wani sai ya tsayar masa da hujja.

7. Wajibi ne muminai su ƙaunaci junansu, su taimaka wa juna, domin duk abin da ya sami ɗaya daga cikinsu, kamar ya same su su duka ne gaba ɗaya.

8. Hana amince wa ma'abota shirka da yarda da su yarda ta gaba ɗaya.

9. Azabar munafuki ta fi ta kafiri. Watau da munafuƙi da kafiri sun yi tarayya a cikin kafirci; amma munafuki ya ɗara kafiri da wani kafircin, shi ne yi wa Musulunci da Musulmi izgili, kuma suna saka rigar Musulunci suna yi wa kafirai aikin leƙen asiri. Da haka Musulmi suke samun babbar matsala ta dalilinsu, sai azabar munafuƙai ta ɗara azabar kafirai.

Suratun Nisa'i (144-147)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ ٱلۡكَٰفِرِينَ أَوۡلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۚ أَتُرِيدُونَ أَن تَجۡعَلُواْ لِلَّهِ عَلَيۡكُمۡ سُلۡطَٰنٗا مُّبِينًا ١٤٤ إِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ فِي ٱلدَّرۡكِ ٱلۡأَسۡفَلِ مِنَ ٱلنَّارِ وَلَن تَجِدَ لَهُمۡ نَصِيرًا ١٤٥ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُواْ وَأَصۡلَحُواْ وَٱعۡتَصَمُواْ بِٱللَّهِ وَأَخۡلَصُواْ دِينَهُمۡ لِلَّهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۖ وَسَوۡفَ يُؤۡتِ ٱللَّهُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَجۡرًا عَظِيمٗا ١٤٦ مَّا يَفۡعَلُ ٱللَّهُ بِعَذَابِكُمۡ إِن شَكَرۡتُمۡ وَءَامَنتُمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ شَاكِرًا عَلِيمًا ١٤٧

144. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi kafirai a matsayin masoya ku bar muminai. Shin kuna so ku ba wa Allah wata hujja mabayyaniya ne a kanku?

145. Lalle munafuƙai suna cikin matakin ƙarshe na can ƙarƙashin wuta, kuma ba za ka taɓa sama musu wani mataimaki ba.

146. Sai fa waɗanda suka tuba, kuma suka gyara aikinsu, kuma suka yi riƙo ga igiyar Allah; kuma suka tsantsanta addininsu don Allah; to waɗannan suna tare da muminai; kuma Allah zai bai wa muminai lada mai girma.

147. Me Allah zai yi da azabtar da ku idan har kun yi godiya kuma kun yi imani? Allah kuwa Ya kasance Mai godiya ne, Mai yawan sani.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa muminai kashedi da su riƙi kafirai masoyansu, suna ƙawance da su, su bar ‘yan’uwansu muminai; yin haka zai ba wa Allah wata hujja bayyananniya ta yi musu uƙuba. Sai kuma ya bayyana makomar munafuƙai da cewa, suna can ƙarƙashin wutar Jahannama, kuma ba wanda zai taimaka ya ceto su daga wannan azabar. Sai dai idan sun tuba sun bar munafunci, sun gyara ayyukansu na fili da na ɓoye, suka tsantsanta addininsu ga Allah shi kaɗai, suka watsar da mugun halinsu na munafunci da riya; to da za su yi haka, da sun dawo cikin muminai, suna tare da su a duniya da lahira, su kuma shiga Aljanna tare. Kuma Allah zai ba wa muminai wani lada mai girma wanda babu wanda ya san haƙiƙaninsa sai Allah shi kaɗai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, me zai sa ya yi wa bayinsa azaba, alhali sun yi godiya bisa ga ni’imominsa, sun yi masa biyayya, kuma sun yi imani na gaskiya? Allah ba shi da wata buƙata ta yin haka. Allah kuma mai godiya ne ga wanda ya gode masa, sai ya ba shi lada fiye da aikinsa, kuma masani ne ga wanda ya yi imani har zuciyarsa, kuma zai saka wa kowa a bisa aikinsa mai kyau ko mummuna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana yayata mummunan zance, wanda kan iya haifar da matsaloli masu yawa a tsakanin al’umma. Zai fara ne da tuhumar wani, daga nan sai ya rikiɗa ya koma ƙiyayya wadda za ta kai ga shiga haƙƙoƙin juna, watakila ma ta kai ga zubar da jini. A ƙarshe wannan ya haifar da rushewar zamantakewar al’umma, mutane su daina yarda da junansu, rashin kiyaye haƙƙoƙi ya zama ruwan dare a cikin al’umma.

2. Musulunci yana kare mutuncin mutum matuƙar bai zalunci wani ba; idan mutum ya zama azzalumi ba shi da sauran mutunci da za a kare masa. Musulunci ya ba da dama ga wanda aka zalunta ya fito ya yi magana ya bayyana irin zaluncin da aka yi masa a gaban alƙali, ko waɗanda za su taimaka masa su ƙwato masa haƙƙinsa.

3. Musulunci addini ne da ba ya son terere da cin mutunci da miyagun ɗabi’u; koyaushe yana nasiha ne da tabbatar da gyara a cikin al’umma. Shi ya sa Musulunci ya haramta yi da wani, wato cin naman ɗan’uwansa.

4. Cikar adalcin Musulunci, yayin da ya ba da dama ga wanda aka zalunta ya fito ya bayyana iya zaluncin da aka yi masa, ba tare da ya yi ƙari ba.

5. Musulunci ya yarda mutum ya bayyana alherin da ya yi da niyyar wasu su yi koyi da shi, ba da niyyar riya ko son a sani ba. Idan ya fahimci zuciyarsa tana karkata zuwa ga riya, to ɓoyewar ce ta fi zama alheri a gare shi.

6. Wanda duk ya yafe wa wani laifin da ya yi masa, to shi ma Allah zai yafe masa nasa.

Suratun Nisa’i (148-152)
۞لَّا يُحِبُّ ٱللَّهُ ٱلۡجَهۡرَ بِٱلسُّوٓءِ مِنَ ٱلۡقَوۡلِ إِلَّا مَن ظُلِمَۚ وَكَانَ ٱللَّهُ سَمِيعًا عَلِيمًا ١٤٨ إِن تُبۡدُواْ خَيۡرًا أَوۡ تُخۡفُوهُ أَوۡ تَعۡفُواْ عَن سُوٓءٖ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَفُوّٗا قَدِيرًا ١٤٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡفُرُونَ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيُرِيدُونَ أَن يُفَرِّقُواْ بَيۡنَ ٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَيَقُولُونَ نُؤۡمِنُ بِبَعۡضٖ وَنَكۡفُرُ بِبَعۡضٖ وَيُرِيدُونَ

أَن يَتَّخِذُواْ بَيۡنَ ذَٰلِكَ سَبِيلًا ١٥٠ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَٰفِرُونَ حَقّٗاۚ وَأَعۡتَدۡنَا لِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٗا مُّهِينٗا ١٥١ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦ وَلَمۡ يُفَرِّقُواْ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ أُوْلَٰٓئِكَ سَوۡفَ يُؤۡتِيهِمۡ أُجُورَهُمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ١٥٢

148. Allah ba Ya son bayyana mummunan zance, sai dai wanda aka zalunce shi. Kuma Allah Ya kasance Mai ji ne, Mai yawan sani.

149. Idan har kuka bayyana wani alheri ko kuka ɓoye shi ko kuma kuka yi afuwa game da wata cutarwa, to lalle Allah Ya kasance Mai yawan afuwa ne, Mai cikakken iko.

150. Lalle waɗanda suke kafirce wa Allah da manzanninsa, kuma suke nufin su nuna bambanci tsakanin Allah da manzanninsa, kuma suna cewa: “Mun yi imani da wasu, mun kuma kafirce wa wasu,” kuma suna son su riƙi wani tafarki tsakanin wannan (imani da kafirci).

151. Waɗannan su ne kafirai na haƙiƙa. Kuma Mun yi wa kafirai tanadin wata azaba mai wulaƙantarwa.

152. Waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa, kuma ba su nuna bambanci tsakanin ɗaya daga cikinsu ba, waɗannan (Allah) zai ba su ladansu. Allah kuma Ya kasance Mai yawan gafara ne, Mai yawan rahama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, ba ya son wani daga bayinsa ya riƙa bayyana wata mummunar magana a kan wani, sai dai mutumin da aka zalunce shi, to shi babu laifi idan ya furta maganar zaluncin da aka yi masa, musamman idan yana so a bi masa haƙƙinsa, kamar yadda ba shi da laifi idan ya yi mummunar addu’a a kan wanda ya zalunce shi. Allah kuwa mai jin duk maganganun mutane ne masu kyau da marasa kyau, kuma masanin duk abin da yake cikin zukatansu na kyakkyawar aniya da mummuna, kuma zai yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya faɗa wa bayinsa cewa, idan suka bayyana wani alheri ko suka ɓoye shi, ko suka yi afuwa ga wanda ya ɓata musu, to su sani shi ma Allah mai yafe wa bayinsa laifuffukansu ne, duk da cewa yana da ikon ya kama su da waɗannan laifukan, don haka su ma su yafe wa waɗanda suka yi musu ba daidai ba, kamar yadda suke so Allah ya yafe musu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dawo kan hukuncin kafiran da suke bijire wa Allah da manzanninsa, suke raba tsakanin Allah da manzanninsa, ta hanyar cewa sun yi imani da Allah, amma ba su yi imani da manzanninsa ba, ko kuma su ce sun yi imani da wasu manzannin, amma ba su yi imani da wasu ba, kuma wai so suke irin wannan imani ya zama wata hanya ce da za ta sada su da Ubangijinsu. Sai Allah ya bayyana cewa, waɗannan su ne kafirai na haƙiƙa: wannan mataki da suka ɗauka ba zai ta taɓa amfana musu komai ba, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tuni ya tanadar musu azaba ta wulaƙanci tana nan tana jiran su, mutuwa ce kawai a tsakaninsu da ita.
To amma muminai waɗanda suka yi imani da manzanni gaba ɗaya, ba su bambanta tsakaninsu ba, to su kam Allah ya yi musu alƙawarin sakamako mai girma saboda imanin da suka yi na gaskiya ne, don haka Allah zai yi musu sakayya a kansa, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbata mai yawan gafara ne, mai yawan jin ƙai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haɗarin tambayar ƙwaƙwa a Musulunci.

2. Duk sa’adda zunubi ya girmama, to uƙubarsa takan zo da gaggawa ne.

3. Daɗuwar kafirci a zuciya yana ƙara sa ta bijire wa shiriya da ƙin karɓar gaskiya.

4. Aikata zunubbai da zalunci yana janyo Allah ya tsananta wa masu aikata su a duniya da lahira, yana hana musu samun alheri na duniya da na lahira.

5. Gwargwadon aikin mutum shi ne gwargwadon sakamakonsa. Sun hana kawunansu daɗin ɗandanon imani, sai Allah ya haramta musu wasu daɗaɗan abubuwa.

6. Bayanin falalar malamai masu aiki da iliminsu.
7. Ilimi hanya ce ta samun imani. Duk sa'adda ilimin mutum yake ƙaruwa, imaninsa da saninsa ga Allah shi ma yana ƙaruwa.

8. Banu Isra'ila sun yi imani bayan an tilasta musu yin sa, ta hanyar ɗaga dutsen Ɗuri a saman kawunansu, saboda haka ne imaninsu ya zama mai rauni, wanda har ya sa suka warware alƙawarinsu tsakaninsu da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

9. Wanda duk ya kafa hujja da ƙaddara, to hujjarsa ta banza ce, kamar yadda Banu Isra'ila suka kafa hujja da cewa, zukatansu ne a rufe, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ƙaryata su.

10. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana nan a raye, Allah ya ɗaukaka shi da gangar jikinsa da ruhinsa zuwa sama, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi Mi'iraji da Annabi Muhammad (ﷺ) zuwa sama da gangar jikinsa da ruhinsa.

11. Duk wani Bayahude ko Banasare sai ya yi imani da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kafin mutuwarsa, a wani ra'ayi na masu tafsiri, ko kuma ana nufin idan Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sauko. Sai dai dalilai na Alƙur'ani sun nuna cewa, wannan imanin da zai yi a lokacin mutuwarsa ba zai yi masa amfani ba, kamar yadda aya ta 158 cikin Suratul An'am ta nuna.

12. Duk masu cin dukiyar riba a cikin wannan al'umma ta Musulmi, to suna kama ne da Yahudawa.

13. Hujja ba ta tsayuwa a kan mutum sai bayan ta je masa, kamar yadda wanda ya yi wani laifi kafin ya san hukuncinsa, ba a kama shi da wannan laifin.

14. Imanin mutum ba zai cika ba har sai ya yi imani da abin da Annabi (ﷺ) ya zo da shi.

Suratun Nisa'i (153-162)

يَسۡـَٔلُكَ أَهۡلُ ٱلۡكِتَٰبِ أَن تُنَزِّلَ عَلَيۡهِمۡ كِتَٰبٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِۚ فَقَدۡ سَأَلُواْ مُوسَىٰٓ أَكۡبَرَ مِن ذَٰلِكَ فَقَالُوٓاْ أَرِنَا ٱللَّهَ جَهۡرَةٗ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلصَّٰعِقَةُ
بِظُلۡمِهِمۡۚ ثُمَّ ٱتَّخَذُواْ ٱلۡعِجۡلَ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُ فَعَفَوۡنَا عَن ذَٰلِكَۚ وَءَاتَيۡنَا مُوسَىٰ سُلۡطَٰنٗا مُّبِينٗا ١٥٣ وَرَفَعۡنَا فَوۡقَهُمُ ٱلطُّورَ بِمِيثَٰقِهِمۡ
وَقُلۡنَا لَهُمُ ٱدۡخُلُواْ ٱلۡبَابَ سُجَّدٗا وَقُلۡنَا لَهُمۡ لَا تَعۡدُواْ فِي ٱلسَّبۡتِ وَأَخَذۡنَا مِنۡهُم مِّيثَٰقًا غَلِيظٗا ١٥٤ فَبِمَا نَقۡضِهِم مِّيثَٰقَهُمۡ وَكُفۡرِهِم بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
وَقَتۡلِهِمُ ٱلۡأَنۢبِيَآءَ بِغَيۡرِ حَقّٖ وَقَوۡلِهِمۡ قُلُوبُنَا غُلۡفُۢۚ بَلۡ طَبَعَ ٱللَّهُ عَلَيۡهَا بِكُفۡرِهِمۡ فَلَا يُؤۡمِنُونَ إِلَّا قَلِيلٗا ١٥٥ وَبِكُفۡرِهِمۡ وَقَوۡلِهِمۡ عَلَىٰ مَرۡيَمَ
بُهۡتَٰنًا عَظِيمٗا ١٥٦ وَقَوۡلِهِمۡ إِنَّا قَتَلۡنَا ٱلۡمَسِيحَ عِيسَى ٱبۡنَ مَرۡيَمَ رَسُولَ ٱللَّهِ وَمَا قَتَلُوهُ وَمَا صَلَبُوهُ وَلَٰكِن شُبِّهَ لَهُمۡۚ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِ
لَفِي شَكّٖ مِّنۡهُۚ مَا لَهُم بِهِۦ مِنۡ عِلۡمٍ إِلَّا ٱتِّبَاعَ ٱلظَّنِّۚ وَمَا قَتَلُوهُ يَقِينَۢا ١٥٧ بَل رَّفَعَهُ ٱللَّهُ إِلَيۡهِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمٗا ١٥٨ وَإِن مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ
إِلَّا لَيُؤۡمِنَنَّ بِهِۦ قَبۡلَ مَوۡتِهِۦۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ يَكُونُ عَلَيۡهِمۡ شَهِيدٗا ١٥٩ فَبِظُلۡمٖ مِّنَ ٱلَّذِينَ هَادُواْ حَرَّمۡنَا عَلَيۡهِمۡ طَيِّبَٰتٍ أُحِلَّتۡ لَهُمۡ وَبِصَدِّهِمۡ

عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ كَثِيرًا ﴿١٦٠﴾ وَأَخۡذِهِمُ ٱلرِّبَوٰاْ وَقَدۡ نُهُواْ عَنۡهُ وَأَكۡلِهِمۡ أَمۡوَٰلَ ٱلنَّاسِ بِٱلۡبَٰطِلِۚ وَأَعۡتَدۡنَا لِلۡكَٰفِرِينَ مِنۡهُمۡ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿١٦١﴾ لَّٰكِنِ ٱلرَّٰسِخُونَ فِي ٱلۡعِلۡمِ مِنۡهُمۡ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَ يُؤۡمِنُونَ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبۡلِكَۚ وَٱلۡمُقِيمِينَ ٱلصَّلَوٰةَۚ وَٱلۡمُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ أُوْلَٰٓئِكَ سَنُؤۡتِيهِمۡ أَجۡرًا عَظِيمًا ﴿١٦٢﴾

153. Ma’abota Littafi (Yahudawa da Nasara) suna tambayar ka cewa, ka saukar musu da wani cikakken littafi daga sama. To haƙiƙa da ma can sun tambayi Musa abin da ya fi wannan girma, da suka ce: “Ka nuna mana Allah a fili,” sai tsawa ta far musu a sanadiyyar zaluncinsu. Sannan kuma suka riƙi ɗan maraƙi abin bauta bayan hujjoji sun zo musu, sai Muka yi (musu) afuwa a kan haka. Kuma Muka bai wa Musa hujja bayyananniya.

154. Kuma Muka ɗaga dutsen Ɗuri a kansu don su karɓi alƙawarinsu, kuma Muka ce da su: “Ku shiga ƙofar (garin) a sunkuye.” Kuma Muka ce da su: “Kada ku ƙetare iyaka (ta kamun kifi) a ranar Asabar,” kuma Muka yi alƙawari mai ƙarfi da su.

155. To saboda warware alƙawarinsu da kafircewarsu ga ayoyin Allah da kuma kashe wasu annabawan ba tare da wani laifi ba da kuma faɗinsu cewa: “Zukatanmu a rufe suke.”A’a, ba haka ne ba, Allah ne Ya rufe su saboda kafircinsu, don haka ba za su yi imani ba sai ɗan kaɗan.

156. Kuma saboda kafircinsu da kuma wata babbar ƙarya da suka yi wa Maryamu.

157. Da kuma faɗarsu cewa: “Lalle mu mun kashe Almasihu Isa ɗan Maryamu Manzon Allah,” alhalin kuwa ba su kashe shi ba, kuma ba su gicciye shi ba, sai dai an kamanta musu (wani da shi ne). Kuma lalle waɗanda suka yi saɓani game da shi (Annabi Isa) suna cikin shakka game da (kashe) shi, ba su da wani ilimi face bin zato. Kuma a haƙiƙanin gaskiya ba su kashe shi ba.

158. Ba haka ba ne, Allah ya ɗaga shi zuwa gare Shi ne. kuma Allah Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima.

159. Kuma babu wani daga Ma’abota Littafi face sai ya yi imani da shi kafin mutuwarsa; kuma a ranar tashin alƙiyama zai zama mai ba da shaida a kansu.

160. To saboda zaluncin waɗanda suka zama Yahudawa, Muka haramta musu daɗaɗan abubuwan da aka halatta musu, kuma saboda suna yawan hana mutane bin hanyar Allah.

161. Da kuma cin riba da suke yi, tare da cewa an hana su cin ta, da kuma yadda suke cin dukiyar mutane ta hanyar cuta, Mun kuwa yi tanadin azaba mai raɗaɗi ga kafirai daga cikinsu.

162. Amma masu zurfin ilimi daga cikinsu da muminai, suna imani da abin da aka saukar maka da abin da aka saukar gabaninka; musamman ma masu tsayar da salla, da kuma masu bayar da zakka, kuma masu imani da Allah da ranar ƙarshe. Waɗannan ba da jimawa ba za Mu ba su lada mai girma.

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wani izgili ne na Yahudawa da Nasara; duk da cewa Allah ya saukar musu da littafi, amma kuma sai suka riƙa yi wa Annabi Muhammadu (ﷺ) tambaya ta ƙure cewa, suna son ya sauko musu da wani littafi cikakke daga sama. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna masa cewa, kada ma ya damu da wannan ta’annati nasu; ai wannan ba sabon abu ba ne a gare su tare da annabawa, domin sun taɓa neman buƙatar da ta fi wannan wajen Annabi Musa

(Amincin Allah ya tabbata a gare shi),inda suka neme shi ya nuna musu Allah ƙuru-ƙuru su gan shi da idanunsu kafin su gaskata shi. To a kan haka sai da Allah ya yi musu uƙuba da wata tsawa ta hallaka su. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da su ta hanyar sake hura musu rai; amma wannan bai hana su sake komawa gidan jiya ba, domin bauta wa ɗan maraƙi suka yi bayan sun ga hujjoji bayyanannu. Amma duk da haka Allah ya yi musu afuwa, kuma ya ba wa Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) hujjoji bayyanannu, masu tabbatar da gaskiyar abin da ya zo musu da shi.
Game da ƙin yin imani da littafin Attaura da Yahudawa suka yi, sai da Allah ya ɗaga dutsen Ɗuri a samansu don ya tsoratar da su a kan lalle su cika alƙawarin da suka ɗauko na za yin aiki da Attaura da ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Haka kuma Allah ya ba da labarin umarnin da ya ba su na cewa, in sun zo shiga Baitul Maƙdis, su shige ta a sunkuye. Da kuma hanin da ya yi musu na kamun kifi a ranar Asabar, ya yi alƙawari mai ƙarfi kan lalle su bi umarninsa, su kuma guji haninsa. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana laifukansu waɗanda suka yi musabbabin la'antar su da ya yi da cewa, ba wani abu ya jawo musu hakan ba, face warware alƙawarin da aka yi da su da kuma kafirce wa ayoyin Allah da kashe annabawa ba tare da wani haƙƙi ba, sannan da cewar da suka yi wai zukatansu a rufe suke, ba sa iya fahimtar komai, alhali kuwa ƙarya ce suke faɗa. Allah ya nuna cewa ya rufe musu zukata ne saboda kafircinsu. Kuma ga shi duk abin da aka nemi su yi imani da shi, sun bijire masa sai ɗan wani abu ƙanƙani a cikinsu. Wasu dalilan kuma da suka jawo musu la'anar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sun haɗa da, ƙage da tuhumar da suka yi wa Maryam (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), na cewa wai zina ta yi ta haifi Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da kuma cewar da suka yi wai sun kashe Isa ɗan Maryam, Manzon Allah. Allah ya ƙaryata su da cewa, ba su kashe shi ba, kuma ba su gicciye shi ba; abin da aka yi shi ne an jefa wa wani daga cikinsu kamanninsa ne, suka zaci shi ne Annabi Isa, suka kama shi suka kashe.
Daga nan sai aka samu saɓani daga cikin Yahudawa da Nasara game da sha'anin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi); wasu na cewa shi ne aka kashe kuma aka gicciye; wasu kuma suka ce wani ne ba shi ba. To wannan dai ya jefa su cikin shakka da ruɗani da ɗimuwa, ba su da wani ilimi game da hakan sai tsantsar zato. Gaskiyar lamarin dai shi ne ba su kashe shi ba, Allah ne ya ɗauke shi zuwa sama, don haka ba su iya cutar da shi da komai ba. Kuma ai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne Gagara-badau, ba mai iya ja da shi, ya fi ƙarfin maƙiyansa, kuma yana da hikima cikin ayyukansa, duk kuma abubuwan da ya zartar, yana ajiye komai ne a muhallinsa da ya dace da shi.
A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gaya mana lokacin bayyanar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) watau sanda zai sauko ƙasa a ƙarshen zamani. A wannan lokaci babu wani daga cikin Yahudu da Nasara face sai ya yi imani da shi kafin mutuwarsa, sannan kuma zai zo a ranar gobe ƙiyama yana mai ba da shaida a kansu game da isar musu da saƙon Allah da kuma ayyukansu da ya gani lokacin da yake cikinsu kafin a ɗauke shi zuwa sama, da lokacin da aka sauko da shi kafin mutuwarsa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Na rantse da wanda raina yake a hannunsa, lokaci ya kusa ɗan Maryam zai sauko cikinku yana mai hukunci mai adalci, ya karya kuros, ya kashe alade, ya soke jiziya, dukiya ta yawaita, har a rasa mai karɓar ta sadaka, har ya zama a lokacin sujjada guda ɗaya ta fi duniya da duk abin da yake cikinta." Sannan sai Abu Huraira ya ce: "In kun ga dama ku karanta faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): "Kuma babu wani Ma'abocin Littafi, face sai ya yi imani da shi kafin mutuwarsa, kuma a ranar alƙiyama zai zama mai ba da shaida a kansu." [Bukhari #3448, da Muslim #155].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, saboda zaluncin Yahudawa da hana mutane bin hanyar Allah a mafi yawancin lokuta, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haramta musu wasu daɗaɗan abubuwa waɗanda da farko ya halatta musu su, domin wannan ya zama uƙuba a gare su saboda laifukansu, da laifin cin dukiyar riba bayan an hana su cin ta, da kuma laifin ƙwace wa mutane

dukiyoyinsu ba tare da wani dalili na shari'a ba. Don haka wanda duk ya kafirta daga cikinsu, Allah ya yi masa tanadin wata azaba mai raɗaɗin gaske.
Daga nan sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zo da bayanin cewa, ba duka Yahudawa ne suka taru suka zama ɗaya ba, daga cikinsu akwai masu ilimi kuma waɗanda suka kafu a cikin ilimi, kuma suke aiki da iliminsu, da waɗanda suka yi imani da Allah da littattafansa da manzanninsa gaba ɗaya. To waɗannan suna yin imani da abin da aka saukar wa Annabi (ﷺ) watau Alƙur'ani, hakanan suna yin imani da littattafan da aka saukar gabanin Annabi (ﷺ), kuma su ne masu tsayar da salla yadda ya kamata, kuma suke ba da zakkar dukiyoyinsu ga waɗanda suka cancanta su ba, kuma su ne masu yin imani da Allah da ranar lahira da abin da zai faru a cikinta. To waɗannan Allah ya yi musu alƙawarin zai ba su wani lada mai girma, wanda shi ne gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ya kamata ga duk wani mai wa'azi ya riƙa yin mu'amala da jama'a irin wadda manzanni suke yi da al'ummominsu, wani lokaci ya yi albishir, wani lokaci ya yi gargaɗi, wani lokaci ya kwaɗaitar, wani lokaci kuma ya tsoratar. Ɗaukar ɓangaren albishir shi kaɗai yakan iya jawo sangarcewa, haka kuma ɗaukan salon tsoratarwa shi kaɗai yakan iya jawo fitar da ƙauna.

2. Bayanin rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa da ya aiko musu da manzanni, ya saukar musu da littattafai.

3. Ambaton jerin gwanon waɗannan annabawan da yabon su da bayanin halayensu zai ƙara wa mumini imaninsa da su, tare da ƙaunar su da koyi da halayensu da sanin haƙƙoƙinsu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wani sashi na annabawan da suka zo bayan Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), saboda shahararsu da kuma girman matsayinsu a wurin Ma'abota Littafi.

5. Na Farko a manzannin Allah shi ne Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

6. Allah yana son yanke wa mutane duk wani hanzari shi ya sa ya aiko manzannin.

Suratun Nisa'i (163-166)
*إِنَّآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ كَمَآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ نُوحٖ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ مِنۢ بَعۡدِهِۦۚ وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَعِيسَىٰ وَأَيُّوبَ وَيُونُسَ وَهَٰرُونَ وَسُلَيۡمَٰنَۚ وَءَاتَيۡنَا دَاوُۥدَ زَبُورٗا ١٦٣ وَرُسُلٗا قَدۡ قَصَصۡنَٰهُمۡ عَلَيۡكَ مِن قَبۡلُ وَرُسُلٗا لَّمۡ نَقۡصُصۡهُمۡ عَلَيۡكَۚ وَكَلَّمَ ٱللَّهُ مُوسَىٰ تَكۡلِيمٗا ١٦٤ رُّسُلٗا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةُۢ بَعۡدَ ٱلرُّسُلِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمٗا ١٦٥ لَّٰكِنِ ٱللَّهُ يَشۡهَدُ بِمَآ أَنزَلَ إِلَيۡكَۖ أَنزَلَهُۥ بِعِلۡمِهِۦۖ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ يَشۡهَدُونَۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا ١٦٦

163. Lalle Mun yi maka wahayi irin wahayin da Muka yi wa Nuhu da kuma annabawan da suka biyo bayansa, kuma Mun yi wahayi ga Ibrahimu da Isma'ila da Ishaƙa da Ya'akubu da kuma jikokin (Ya'akubu) da Isa da Ayyuba da Yunusa da Haruna da Sulaimanu; kuma Muka bai wa Dawuda littafin Zabura.

164. (Muka) kuma aiko manzanni waɗanda Muka ba ka labarinsu tun da farko, da waɗansu manzannin daban da ba Mu ba ka labarinsu ba; kuma Allah Ya yi magana da Musa kai-tsaye.

165. Manzanni ne masu albishir kuma masu gargaɗi, domin kada mutane su sami wata hujja a wurin Allah bayan aiko manzannin. Kuma Allah Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima.

166. Amma Allah Yana shaida game da abin da Ya saukar maka; Ya saukar da shi ne da iliminsa; haka mala'iku ma suna shaidawa. Kuma Allah Ya isa Mai shaida.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, ya saukar masa da wahayi irin wanda ya saukar wa Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kuma annabawan da suka zo bayan Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kuma Allah ya saukar da wahayi ga Annabi Ibrahimu da 'ya'yansa Annabi Isma'ila da Annabi Ishaƙ da Annabi Ya'aƙubu ɗan Annabi Ishaƙ, da kuma annabawan da suke cikin zurriyar Annabi Ya'aƙubu, da kuma Annabi Isa da Annabi Ayuba da Annabi Yunusa da Annabi Haruna da Annabi Sulaimanu (amincin Allah ya tabbata a gare su baki ɗaya), kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabi Dawudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) littafin Zabura.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, ba duk manzannin Allah ya san labarinsu ba; daga cikinsu akwai waɗanda Allah ya ba shi labarinsu a cikin Alƙur'ani tun gabanin wannan ayar ta sauka, akwai kuma waɗanda bai ba shi labarinsu ba, don haka bai san komai a kansu ba. Kuma Allah ya yi magana da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) magana ta haƙiƙa, ba tare da ɗan saƙo ba. To waɗannan manzanni duk Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko su ne don su zama masu yin albishir ga waɗanda suka yi imani, suka yi musu biyayya, da kyakkyawan sakamako duniya da lahira, sannan su yi gargaɗi ga waɗanda suka kafirce suka bijire musu da azabar Allah a duniya da lahira. Kuma babu sauran wani hanzari da mutane za su kawo don kafa wa Allah hujja da shi bayan aiko da manzanni. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne Gagara-badau, mai murƙushe duk wani maƙiyinsa, kuma mai hikima ne cikin duk lamuransu, wanda yana daga cikin hikimominsa, aiko da manzanni da ya yi zuwa ga mutum da aljan, don ya yanke musu duk wani hanzari da za su iya kawowa a gaban Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ranar gobe ƙiyama, su ce da ya aiko musu da manzanni, da sun yi musu biyayya, kamar yadda ya faɗa a *Suratu Ɗa Ha*, aya ta 134.

An karɓo daga Mughira ɗan Shu'uba (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Babu wani mai son yanke hanzari kamar Allah, saboda haka ne ma ya aiko (manzanni) masu bushara masu gargaɗi." [Bukhari #7416, da Muslim #1499].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, idan har kafirai sun bijire masa, sun ƙi yarda da gaskiyar da ya zo da ita, suna tuhumarsa, to su sani cewa, Allah shi ne yake masa shaida a kan Alƙur'anin da ya saukar masa cewa, Allah ya saukar masa shi ne da iliminsa. Hakanan su ma mala'iku dukansu shaidu ne a kan gaskiyarsa da manzancinsa da gaskiyar Alƙur'anin da aka saukar masa, don haka kada kafircin kafirai ya dame shi, Allah ya isa shaida a kan gaskiyar duk abin da ya saukar masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirci da zalunci sukan lulluɓe zuciyar bawa har ya kasa gane hanyar shiriya ya bi ta.

2. Imani alheri ne duniya da lahira. Duk wani kyakkyawan sakamako na kusa ko na nesa, to imani ne sanadiyyarsa; nasara da shiriya da ilimi da aiki da shi da farin ciki da samun gidan Aljanna duk imani ne sanadiyyar samuwarsu.

3. Saƙon Annabi (ﷺ) ya shafi dukkan halitta gaba ɗaya.

4. Abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi shi ne gaskiya, ba duk abin da aka jingina masa ba.

Suratun Nisa'i (167-170)

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ قَدۡ ضَلُّواْ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ١٦٧ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَظَلَمُواْ لَمۡ يَكُنِ ٱللَّهُ لِيَغۡفِرَ لَهُمۡ وَلَا لِيَهۡدِيَهُمۡ
طَرِيقًا ١٦٨ إِلَّا طَرِيقَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٗا ١٦٩ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدۡ جَآءَكُمُ ٱلرَّسُولُ بِٱلۡحَقِّ مِن رَّبِّكُمۡ فَـَٔامِنُواْ
خَيۡرٗا لَّكُمۡۚ وَإِن تَكۡفُرُواْ فَإِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ١٧٠

167. Lalle waɗanda suka kafirta, kuma suka kange mutane daga hanyar Allah, haƙiƙa sun ɓace ɓata mai nisa.
168. Lalle waɗanda suka kafirta, kuma suka yi zalunci, Allah ba zai taɓa yi musu gafara ba, ba kuma zai shiryar da su wata hanya ta gari ba.

169. Sai dai hanyar wutar Jahannama, suna masu dawwama a cikinta har abada. Yin hakan kuwa ya kasance abu ne mai sauƙi a wajen Allah.

170. Ya ku mutane, haƙiƙa Manzo ya zo muku da gaskiya daga wajen Ubangijinku, don haka ku yi imani shi ya fi alheri a gare ku. Idan kuwa kuka kafirce, to lalle abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa duk na Allah ne. kuma Allah Ya kasance Mai yawan sani ne, Mai hikima.

A nan ma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayani ne a kan kafiran da suka bijire wa gaskiya, suka kuma hana mutane su ba da gaskiya; waɗannan sun ɓata ɓata mai nisan gaske. Ya kuma tabbatar da cewa, waɗannan sun cuci kawunansu kuma ba zai taɓa gafarta musu ba, balle ya datar da su ga bin hanyar gaskiya wadda za ta kai su ga samun gidan Aljanna, sai dai zuwa ga bin hanyar ɓata wadda za ta kai su ga shiga wutar Jahannama, su dawwama a cikinta har abada. Kuma wannan al'amari ne mai sauƙi a wurin Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗakar da mutane baki ɗaya, yana mai cewa, duk abin da Annabi (ﷺ) ya zo musu da shi daga Allah gaskiya ne, don haka lalle su yi imani da shi; yin haka shi ne alheri a gare su duniya da lahira. Idan kuma sun ƙi sun kafirce to fa ba za su ragi Allah da komai ba, domin shi mawadaci ne, ba shi da wata buƙata a wajensu, shi ne mamallakin sammai da ƙasa, kuma shi mai cikkaken ilimi ne kuma mai cikakkiyar hikima ne da yake ajiye komai a inda ya dace. Don haka ya san wanda ya cancanci shiriya, ya kuma shiryar da shi, kuma ya san wanda ya cancanci ɓata, ya kuma ɓatar da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wuce iyaka a cikin lamarin addini wanda ya shafi Annabi (ﷺ), ko yake da alaƙa da ibada wannan haramun ne. Wanda yake son Annabi (ﷺ), bai halatta ya ba shi siffofin Allah, ko ya jingina masa aikin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba, duk wanda ya yi haka, to ya aikata abin da Allah da Manzonsa suka hana.

2. Duk wanda ya dogara da Allah, to zai ishe shi a komai.

3. Gargaɗi game da girman kai da bayanin azabar da Allah ya tanadar wa masu girman kai a kan bautarsa.

4. Wanda duk ya kasance mai imani na gaskiya, to tabbas zai zama mai dogaro ne da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Tabbatar da manzancin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da zama bawan Allah da kuma cewa shi ba Allah ne ba.

Suratun Nisa'i (171-175)

يَـٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَا تَغۡلُواْ فِي دِينِكُمۡ وَلَا تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡحَقَّۚ إِنَّمَا ٱلۡمَسِيحُ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ رَسُولُ ٱللَّهِ وَكَلِمَتُهُۥٓ أَلۡقَىٰهَآ إِلَىٰ مَرۡيَمَ
وَرُوحٞ مِّنۡهُۖ فَـَٔامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦۖ وَلَا تَقُولُواْ ثَلَٰثَةٌۚ ٱنتَهُواْ خَيۡرٗا لَّكُمۡۚ إِنَّمَا ٱللَّهُ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ سُبۡحَانَهُۥٓ أَن يَكُونَ لَهُۥ وَلَدٞۘ لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلٗا ١٧١ لَّن يَسۡتَنكِفَ ٱلۡمَسِيحُ أَن يَكُونَ عَبۡدٗا لِّلَّهِ وَلَا ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ ٱلۡمُقَرَّبُونَۚ وَمَن يَسۡتَنكِفۡ عَنۡ عِبَادَتِهِۦ
وَيَسۡتَكۡبِرۡ فَسَيَحۡشُرُهُمۡ إِلَيۡهِ جَمِيعٗا ١٧٢ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَيُوَفِّيهِمۡ أُجُورَهُمۡ وَيَزِيدُهُم مِّن فَضۡلِهِۦۖ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱسۡتَنكَفُواْ
وَٱسۡتَكۡبَرُواْ فَيُعَذِّبُهُمۡ عَذَابًا أَلِيمٗا وَلَا يَجِدُونَ لَهُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ١٧٣ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدۡ جَآءَكُم بُرۡهَٰنٞ مِّن رَّبِّكُمۡ وَأَنزَلۡنَآ
إِلَيۡكُمۡ نُورٗا مُّبِينٗا ١٧٤ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَٱعۡتَصَمُواْ بِهِۦ فَسَيُدۡخِلُهُمۡ فِي رَحۡمَةٖ مِّنۡهُ وَفَضۡلٖ وَيَهۡدِيهِمۡ إِلَيۡهِ صِرَٰطٗا مُّسۡتَقِيمًا ١٧٥

171. Ya ku Ma'abota Littafi, kada ku wuce iyaka cikin addininku, kuma kada ku faɗi wata magana game da Allah sai ta gaskiya. Almasihu Isa ɗan Maryamu Manzon Allah ne, kuma kalmarsa ce da ya jefa wa Maryamu, kuma Ruhi ne daga gare Shi; don haka ku yi imani da Allah da manzanninsa, kuma kada ku ɾika cewa su uku ne. Ku daina shi ya fi alheri a gare ku. Allah Shi ne kaɗai abin bauta da gaskiya, Ɗaya ne; Ya tsarkaka a ce Yana da ɗa. Kuma abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne, kuma Allah Ya isa Abin dogaro.

172. Almasihu ba zai taɓa ƙyamar ya zama bawan Allah ba, hakanan su ma mala'iku makusanta. Duk wanda yake ƙyamar bautar Allah, kuma suke girman kai, to zai tattara su gaba ɗaya zuwa gare Shi.

173. To amma waɗanda suka yi imani, kuma suka yi ayyuka nagari, to zai cika musu ladansu, kuma Ya ƙara musu daga falalarsa. Amma waɗanda suka ƙyamaci bautar Allah kuwa, suka kuma yi girman kai, to zai azabtar da su azaba mai raɗaɗi, kuma ba za su taɓa samun wani masoyi ko mataimaki ba Allah ba.

174. Ya ku mutane, haƙiƙa hujja ta zo muku daga Ubangijinku, kuma Mun saukar muku wani haske mabayyani.

175. To amma waɗanda suka yi imani da Allah kuma suka yi garkuwa da Shi, to zai shigar da su cikin wata rahama tasa da kuma wata falala, kuma Ya shiryar da su tafarki madaidaici zuwa gare Shi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gargaɗin Nasara ne, a kan wuce iyaka da suke yi wajen kuzuzuta lamarin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) har ta kai su ga cewa wai ɗan Allah ne. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, wannan ƙage ne suke yi wa Allah, domin shi ya fi ƙarfin a ce yana da mata balle ɗa. Shi kuwa Annabi Isa Almasihu ɗan Maryamu Manzon Allah ne, shi ya halicce shi ta hanyar kalmar da ya jefa ga Maryam (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), don haka lalle su yi imani da shi a matsayin bawan Allah, kuma Manzonsa, kamar yadda aka umarce su da su yi imani da Allah da duk manzanninsa, kada su ɾika cewa alloli uku ne, wato su mayar da Isa da mahifiyarsa ababen tarayya da Allah.

An karɓo daga Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Kada ku kuzuzuta lamarina kamar yadda Nasara suka kuzuzuta lamarin Isa ɗan Maryam. Ni bawan Allah ne kawai, don haka ku ce: Bawan Allah kuma Manzonsa.” [Bukhari #3445].

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya zo yana yi wa Manzon Allah (ﷺ) kirari, yana cewa: “Ya Muhammadu, ya Shugabanmu, ya ɗan Shugabanmu, ya mafi alherinmu, ya ɗan mafi alherinmu.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ya ku mutane, ku lura da abin da kuke faɗa, kada Shaiɗan ya yi muku wasa da zukatanku. Ni Muhammadu ne ɗan Abdullahi, bawan Allah ne kuma Manzonsa, Wallahi ba na son ku ɗaga ni sama da matsayina da Allah ya ajiye ni.” [Ahmad #12573, da An-Nasa’i, *As-Sunan Al-Kubra* #10006, da Ibn Hibban #2640].

An karɓo daga Ubadatu ɗan Samit (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Duk wanda ya shaida babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah, kuma shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya, kuma Muhammadu bawansa ne Manzonsa, kuma Isa bawan Allah ne kuma Manzonsa, kuma kalmarsa ce da ya jefa ta ga Maryamu, kuma Ruhi ne daga gare shi, kuma ya shaida Aljanna gaskiya ce, wuta ma gaskiya ce, to Allah zai shigar da shi Aljanna bisa aikinsa da ya kasance a kai na ƙwarai.” [Bukhari #3435, da Muslim #28].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da yi wa Nasara kashedi da cewa, su bar wannan mummunar aƙidar da suke kai na cewa, Isa ɗan Allah ne ko Allah uku ne, barin wannan aƙida shi ne alheri gare su, domin babu wani abin bauta na gaskiya sai Allah shi kaɗai, kuma ya tsarkaka a ce yana da ɗa. Me zai yi da ɗa, alhalin duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙassai nasa ne, halittarsa ce kuma bayinsa ne? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya isa abin dogaro, shi ne mai kula da kowa da komai, mai gudanar da al’amuran bayinsa ba tare da ya buƙaci taimakon wani ba, don haka me zai sa ya riƙi mata ko ɗa?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, su da suke irin wannan azarɓaɓi dangane da sha’anin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba su san cewa, shi da kansa bai taɓa ƙyamar ya zama bawan Allah ba, domin zamansa bawan Allah wata ɗaukaka ce gare shi. Su Mala’iku ba su taɓa ƙyamar bautar Allah ba. Don haka duk wanda ya ƙyamaci bautar Allah, to ya sani ya cuci kansa, Allah zai tattaro su gaba ɗaya ya hukunta su da irin hukuncin da suka cancanta. To amma wanda ya yi imani, kuma ya yi aiki na ƙwarai, to shi kam Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ba shi cikakken ladansa daga yalwatacciyar falalarsa har ma da ƙari. Su kuma masu girman kai su ƙi bauta masa, Allah zai ɗanɗana masa azaba mai raɗaɗi, kuma ba su da wani mataimaki in ba Allah ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fuskantar da bayani zuwa ga mutane gaba ɗaya da cewa, hujjoji da dalilai ƙwarara sun zo musu, waɗanda suke bayyana ƙarya da gaskiya. Alƙur’ani mai haske ne ya nuna wa mutane hanya. Muminai waɗanda suka ba da gaskiya da Allah, kuma suka riƙe wannan hanyar da ƙarfi, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin zai shigar da su cikin rahamarsa da falalarsa da kuma samun yardarsa.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗayin sahabbai wajen neman ilimi.

2. Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) wata tambayar ba ya sanin amsar ta, don haka yakan jinkirta bayar da amsa a kanta har sai an saukar masa da wahayi.

3. Girman sha’anin fatawa a addini. Don haka duk wanda ya sami kansa cikin fagen ba da fatawa, to lalle ya yi taka-tsantsan, domin yana wakiltar Allah ne a kan abin da yake yin fatawa da shi.

Suratun Nisa’i (176)

يَسْتَفْتُونَكَ قُلِ ٱللَّهُ يُفْتِيكُمْ فِي ٱلْكَلَٰلَةِۚ إِنِ ٱمْرُؤٌاْ هَلَكَ لَيْسَ لَهُۥ وَلَدٌ وَلَهُۥٓ أُخْتٌ فَلَهَا نِصْفُ مَا تَرَكَۚ وَهُوَ يَرِثُهَآ إِن لَّمْ يَكُن لَّهَا وَلَدٌۚ فَإِن كَانَتَا ٱثْنَتَيْنِ فَلَهُمَا ٱلثُّلُثَانِ مِمَّا تَرَكَۚ وَإِن كَانُوٓاْ إِخْوَةً رِّجَالًا وَنِسَآءً فَلِلذَّكَرِ مِثْلُ حَظِّ ٱلْأُنثَيَيْنِۗ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ أَن تَضِلُّواْۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيْءٍ عَلِيمٌ ١٧٦

176. Suna neman ka yi musu fatawa, ka ce: “Allah ne zai yi muku fatawa game da *kalala*. Idan mutum ya mutu ba shi da ɗa ko ‘ya, amma yana da ‘yar’uwa mace, to za a ba ta rabin abin da ya bari. Shi kuwa zai gaje (dukiyar) ta gaba ɗaya idan ya kasance ba ta da ɗa ko ‘ya. Amma idan suka kasance mata ne su biyu, to suna da biyu bisa uku na abin da ya bari. Idan kuwa sun kasance ‘yan’uwa masu yawa maza da mata, to duk namiji ɗaya yana da rabon mata biyu.” Allah Yana bayyana muku wannan ne don kar ku ɓace. Kuma Allah Masanin komai ne.

A ayar ƙarshe ta wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana amsa fatawar da sahabban Annabi suke yi masa game da hukuncin gadon kalala, wato wanda ya mutu bai bar ɗa ko iyaye masu cin gadonsa ba. To sai Allah ya umarci Manzonsa da cewa shi ne zai ba su fatawa a kan wannan tambayar. Idan mutum ya mutu bai bar ‘ya’ya ko iyaye ba, sai ‘yar’uwarsa shaƙiƙiya ko li’abbiya, to za ta ci gadon rabin dukiyar da ya bari. Idan kuwa ita ce ta mutu kafin ɗan’uwanta, kuma ba ta bar ‘ya’ya ko iyaye masu cin gadonta ba, to shi zai ci gadon dukiyarta gaba ɗaya. Idan akwai wani mai cin gado tare da shi, kamar miji, to sai a ba shi kasonsa, shi kuma ɗan’uwan nata ya kwashe ragowar gadon.
To amma kuma idan ‘yan’uwan nasa mata su biyu ne ko fiye da biyu, to za su ci gadon kaso biyu bisa uku na abin da ɗan’uwansu ya bari. Idan kuwa ‘yan’uwan da ya bari masu yawa ne maza da mata, to sai a ba namiji daga cikinsu kason mata biyu. Allah yana yi wa mutane bayanin hukunce-hukuncensa ne don kada su ɓata. Allah kuma masanin komai ne.

An karɓo daga Albara (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Surar ƙarshe da ta sauka ita ce Suratu Bara’ah, kuma aya ta ƙarshe da ta sauka ita ce wannan ayar.” [Bukhari #4605].

An fassara wannan hadisi da cewa, yana nufin ƙarshe hukunce-hukuncen gado da aka saukar a Alƙur’ani. [Dubi, Alƙasɗalani, *Irshadus Sari*, Juzu’i na 7 shafi na 100].

An karɓo daga Jabiru ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Na yi rashin lafiya, sai Manzon Allah (ﷺ) da Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) suka tako da ƙafa duba ni. Sai na suma, sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi alwala ya zuba mini sauran ruwan alwalarsa, sai na farɗaɗo. Na ce: “Ya Manzon Allah, yaya zan yi hukunci game da dukiyata?” Sai bai ba ni wata amsa ba, har sai da wannan ayar ta sauka: “Suna yi maka fatawa. Ka ce: “Allah zai yi muku fatawa game da kalala.” [Bukhari #6723, da Muslim #1616].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wata yarjejeniya wadda ba ta saɓa wa shari’a ba, wadda mutum biyu ko fiye ko ɓangarori biyu za su ƙulla, to wajibi ne kowa ya riƙe ta kada ya karya ta da gangan.

2. Wajibi ne ga mumini ya miƙa wuya ga hukuncin Allah, ba tare da jayayya ko ɓata rai ba.

3. Faɗakarwa a kan girmama wuraren ibada masu alfarma da watanni masu alfarma, domin girmama su girmama Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne.

4. Musulunci yana umartar ‘ya’yansa da su zama masu adalci hatta ga maƙiyansu waɗanda suka cuce su. Kada ƙiyayyar macuci ta kai su ga hana masa haƙƙinsa ko ƙetare iyaka wajen karɓo haƙƙinsu da yake hannunsa, ta hanyar ƙwatar fiye da abin da ya halatta a karɓa daga wajensa. Domin Musulunci yana so ‘ya’yansa su zama daban wajen kyawawan halaye da ɗabi’u, ta yadda maƙiyi zai fahimci haƙiƙanin koyarwar addinin Musulunci daga halayyar Musulmi su kansu.

5. Musulunci yana kira zuwa ga samun taimakon juna cikin al’umma a kan ayyukan alheri domin gina nagartacciyar al’umma a bayan ƙasa, kamar yadda ya haramta duk wani aikin haɗin kai wajen saɓa wa Allah da Manzonsa (ﷺ) ko cutar da wasu.

5-Suratul Ma'ida

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna *'Suratul Ma'ida'*, saboda a cikin ta an kawo bayanin *'Ma'ida*', wato kaɓaki na abinci wanda *Hawariyyuna* almajiran Annabi Isa suka nemi ya roƙi Allah a saukar musu da shi don su ci daga gare shi kuma su ƙara yarda da ingancin annabcinsa.

An karɓo daga Jubairu ɗan Nufairu (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: "Na je hajji sai na shiga wajen A'isha (Allah ya kara mata yarda) sai ta ce mini: "Ya Jubairu, kana karanta *Al-Ma'ida*?" Sai na ce: "E." Sai ta ce: 'Lalle ita ce ƙarshen Surar da ta sauka.'…." [Ahmad #25547, da Nasa'i, *As-Sunan Al-Kubra* #1073].
Ana kiran ta da *'Suratul Uƙūd'*, domin zuwan wannan lafazin a farkon Surar.

2. Sanda Ta Sauka:
Malamai sun haɗu a kan cewa a Madina aka saukar da ita.
Hadisin Jubairu ɗan Nufairu daga A'isha (Allah ya kara mata yarda) ya gabata.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tis'in da ɗaya (91) a jerin saukar surori. Ta sauka bayan *'Suratul Ahzab'*, gabanin *'Suratul Mumtahana*'.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin yawancin malamai ayoyinta ɗari ne da ashirin da biyu (122), amma a lissafin mutanen Basra adadinsu ɗari ɗaya ne da ashirin da uku (123), a wurin mutanen Kufa kuwa ayoyinta ɗari ne da ashirin (120) daidai.

5. Falalarta:
Tana daga cikin dogwayen Surori da aka ba wa Annabi (ﷺ) maimakon At-Taura:
An karɓo daga Wasila ɗan Al-Asƙa' (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "A madadin Attaura an ba ni dogwayen surori bakwai. A madadin Zabura kuwa an ba ni surori masu ayoyi ɗari (ko ɗoriya). A madadin Linjila kuwa an ba ni *Al-Masani*. Sannan an fifita ni da (surorin) *Mufassal*."
Tana daga cikin abin da ya sauka na ƙarshe a Alƙur'ani:
An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Surar ƙarshe da ta sauka ita ce *'Suratul Ma'ida'*." [Tirmizi #3063].

6. Babban Jigonta:
• Ƙarfafa batun cika alƙawari da yarjejeniya.
• Bayanin wasu al'amuran aƙida masu yawa.
• Bayanin wasu da dama daga cikin hakunce-hukuncen shari'a.
• Tsara alaƙa tsakanin Musulmai da waɗanda ba Musulmai ba.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:

• Tabbatar da ingantacciyar aƙida da ba wa mas'alolin Tauhidi muhimmanci da tunatarwa game da ranar alƙiyama.

• Gargaɗi a kan jiɓintar waɗanda ba Musulmi ba da bayanin cewa munafukai su ne suka fi saurin rungumar kafirai.

• Tsara alaƙa tsakanin Musulmi da waɗanda ba Musulmi ba, musamman ma Yahudu da Nasara.

• Bayanin wasu daga cikin hukunce-hukuncen shari'a masu alaƙa da ibada ko mu'amala, kamar hukunce-hukuncen yarjejeniya da yanka da farauta da ihrami da auren mace Bakitabiya da hukuncin ridda da na tsarki da haddin sata da ta'addanci da yaɗa ɓarna a bayan ƙasa da haramcin giya da caca da kaffarar rantsuwa da wasiyya lokacin mutuwa da sauransu.

• Surar ta ƙunshi wasu labarai na Banu Isra'ila tare da Annabi Musa, da ƙissar 'ya'yan Annabi Adamu da ƙissar saukar da kaɓaki ga Banu Isra'ila.

• Bayanin wasu daga cikin miyagun halayen Yahudawa da Nasara kamar karya alƙawari da canja Littattafan Allah da jingina wa Allah ɗa da ƙaryata manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ).

Suratul Ma'ida (1-2)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَوۡفُواْ بِٱلۡعُقُودِۚ أُحِلَّتۡ لَكُم بَهِيمَةُ ٱلۡأَنۡعَـٰمِ إِلَّا مَا يُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡ غَيۡرَ مُحِلِّي ٱلصَّيۡدِ وَأَنتُمۡ حُرُمٌۗ إِنَّ ٱللَّهَ يَحۡكُمُ مَا يُرِيدُ ۝١ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُحِلُّواْ شَعَـٰٓئِرَ ٱللَّهِ وَلَا ٱلشَّهۡرَ ٱلۡحَرَامَ وَلَا ٱلۡهَدۡيَ وَلَا ٱلۡقَلَـٰٓئِدَ وَلَآ ءَآمِّينَ ٱلۡبَيۡتَ ٱلۡحَرَامَ يَبۡتَغُونَ فَضۡلٗا مِّن رَّبِّهِمۡ وَرِضۡوَٰنٗاۚ وَإِذَا حَلَلۡتُمۡ فَٱصۡطَادُواْۚ وَلَا يَجۡرِمَنَّكُمۡ شَنَـَٔانُ قَوۡمٍ أَن صَدُّوكُمۡ عَنِ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِ أَن تَعۡتَدُواْۘ وَتَعَاوَنُواْ عَلَى ٱلۡبِرِّ وَٱلتَّقۡوَىٰۖ وَلَا تَعَاوَنُواْ عَلَى ٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡعُدۡوَٰنِۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ۝٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku cika alƙawura. An halatta muku dabbobin ni'ima, sai dai abin da ake karanta muku (haramcinsa), ba kuna masu halatta farauta ba alhalin kuna cikin Harami, lalle Allah Yana hukunta abin da Yake nufi.

2. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku halatta keta alfarmar alamomin addinin Allah, ko (ku wulaƙanta) Wata mai alfarma ko dabbobin hadaya ko dabbobin hadaya masu alama da (tare) masu nufin ziyarar Ɗaki mai alfarma, suna neman falala daga wurin Ubangijinsu da yardarsa. Idan kuwa kuka kwance Harami, to ku yi farauta (idan kuna so). Kuma kada ƙiyayyar wasu mutane da suka hana ku isa masallaci mai alfarma, ta sa ku yi ta'addanci. Kuma ku taimaki juna a kan aikin alheri da taƙawa; kada kuma ku taimaka wa juna a kan ayyukan saɓo da ta'addanci. Kuma ku kiyaye dokokin Allah; lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar ne da umartar muminai kansu riƙa cika alƙawurran da suka ɗauka tsakaninsu da Allah da waɗanda suke tsakaninsu da 'yan'uwansu mutane, amma alƙawuran da ba su saɓa wa shari'a ba. Sannan kuma ya bayyana musu cewa, ya halatta musu dabbobin ni'ima, irin su raƙuma da shanu da ƙananan dabbobi, sai dai waɗanda za a yi musu bayanin su nan gaba a aya ta 3. Kuma ba a halatta musu yin farauta ba lokacin da suke sanye haramin hajji ko umara, ko kuma sanda suke cikin Haramin Makka da Madina. Allah kuma yana hukunta abin da ya yi nufi ne, ya kuma zartar da hukuncin da ya ga dama.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya haramta wa muminai ƙetare iyakokinsa ta hanyar wulaƙanta abubuwa masu alfarma waɗanda ya yi umarnin a girmama su na addini, kamar ayyukan hajji da umra da kuma watannin nan masu alfarma, watau Shawwal da Zulƙi'ida da Zulhijja da Rajab, ta hanyar yin yaƙi a cikinsu ko aikata zalunci ko wasu laifuffuka. Hakanan ya haramta musu keta alfarmar dabbobin da aka

ware don hadaya ta hanyar su yanka su kafin su ƙarasa mayankansu, ko kuma su hana dabbobin ƙarasawa can; haka kuma dabbobin da aka yi musu alamomi da rataye a wuyansu domin nuna cewa an keɓance su don yankan hadaya. Hakanan Allah ya hana muminai yaƙar waɗanda suka taho domin ziyarar Ɗakin Ka'aba don neman falarar Allah da yardarsa, wato masu niyyar hajji da umara ko niyyar kasuwanci, saboda duk wanda ya shiga garin Makka, to ya zama amintacce. Amma kuma Allah ya halatta musu su yin farauta yayin da suka sauke hiraminsu na hajji ko na umara da kuma lokacin da suka fita daga Haramin Makka ko Madina.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kada ƙiyayyar mutanen da suka cuce su suka hana su shiga garin Makka ta sa su su zalunce su ko su yi musu ta'addanci, domin shi mumini dole ne a komai ya ji tsoron Allah, kuma ya zama mai gaskiya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su taimaki junansu a kan aikin alheri da taƙawa, kada su taimaki juna a kan aikata zunubi da zalunci, ya umarce su da su ji tsoron Allah ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da shi da barin abin da ya hana. Lalle Allah mai tsananin uƙuba ne ga duk wanda ya saɓa masa.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman haɗarin shirka, wadda take yin tasiri har a kan sha'anin yanka.

2. Tasirin niyya a kan aiki. Don haka duk abin da aka yanka don wanin Allah, ya zama haramun, ko da kuwa an ambaci sunan Allah a kai.

3. Bai halatta Musulmi su bar addininsu ba don suna jin tsoron kafirai.

4. Duk abin da Allah ya haramta, ya zama haramun, ko da mutum bai gano hikimar haramtawar ba, domin Allah yana haramta wa bayinsa duk abin da zai cutar da lafiyarsu da rayuwarsu.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haramta neman sa'a da akan yi da kibau, domin ya nuna cewa duk wani camfi ko wani siddabaru ba shi da gurbi a addinin Musulunci, kuma babu mai yarda da shi sai mai raunin imani da hankali, marar basira. Shi ya sa Musulunci ya haramta camfi da bokanci da duba da bugun ƙasa da sauransu.

6. Addinin Musulunci ya cika tun lokacin da wannan ayar ta sauka, mai cewa: "A yau na cika muku addininku...." Duk abin da bai zama addini ba kafin saukar da wannan ayar, to ba zai taɓa zama addini ba bayan saukarta. Don haka duk wata bidi'a a addini ɓata ce, aiki da ita yana cin karo da wannan ayar. Shi ya sa Imamu Malik (Allah ya kara masa yarda) yake cewa: "Duk wanda ya ƙirƙiri wani sabon abu a wannan addini, wanda magabatan wannan al'umma ba su san shi ba, to wannan yana ganin Annabi (ﷺ) ya ci amanar manzanci, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana cewa: "....A yau ne na cika muku addininku, kuma na cika muku ni'imata, kuma na yardar muku Musulunci ya zamo addininku." To duk abin da ba zai zama addini a waccan rana ba, to a yau ma ba zai taɓa zama addini ba." [Ibn Hazm, *Al-Ihkam*, Juzu'i na 6, Shafi na 58 da As-Shaɗibi, *Al-I'itisam*, Juzu'i na 1, Shafi na 494].

7. Shari'ar Allah wani dunƙulallen tsari ne wanda bai yiwuwa a yi masa gunduwa-gunduwa, a yarda da wani ɓangare, a yi watsi da wani; dole ne a yarda da shi a dunƙulensa, musamman abin da ya shafi aƙida da ibada da mu'amala ta zamantakewar mutum da iyalinsa ko ta al'umma ko ta ƙasa da ƙasa. Duk waɗannan abubuwa a dunƙule su ake cewa 'addini', su ne kuma abin da Allah ya ce ya cika shi, kuma shi ne ni'imar da ya ce ya cika ta. Waɗannan abubuwa a jumlace su ne tsarin rayuwa wadda Allah ya yarje wa muminai su rayu a kanta.

8. Musulunci shi ne mafi girman ni’imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa wannan al’umma. Duk wanda ya saki wannan addini na Musulunci, ko ya ƙi karɓar sa, to ya haramta wa kansa rayuwa cikin ni’ima, ya zaɓi rayuwar musifa da wulaƙanci da ƙunci a duniya da lahira.

Suratul Ma’ida (3)

حُرِّمَتْ عَلَيْكُمُ ٱلْمَيْتَةُ وَٱلدَّمُ وَلَحْمُ ٱلْخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ لِغَيْرِ ٱللَّهِ بِهِۦ وَٱلْمُنْخَنِقَةُ وَٱلْمَوْقُوذَةُ وَٱلْمُتَرَدِّيَةُ وَٱلنَّطِيحَةُ وَمَآ أَكَلَ ٱلسَّبُعُ إِلَّا مَا ذَكَّيْتُمْ وَمَا ذُبِحَ عَلَى ٱلنُّصُبِ وَأَن تَسْتَقْسِمُواْ بِٱلْأَزْلَٰمِ ۚ ذَٰلِكُمْ فِسْقٌ ۗ ٱلْيَوْمَ يَئِسَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن دِينِكُمْ فَلَا تَخْشَوْهُمْ وَٱخْشَوْنِ ۚ ٱلْيَوْمَ أَكْمَلْتُ لَكُمْ دِينَكُمْ وَأَتْمَمْتُ عَلَيْكُمْ نِعْمَتِى وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلْإِسْلَٰمَ دِينًا ۚ فَمَنِ ٱضْطُرَّ فِى مَخْمَصَةٍ غَيْرَ مُتَجَانِفٍ لِّإِثْمٍ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٣﴾

3. An haramta muku (cin) mushe da jini da naman alade da abin da aka yanka shi da sunan wanin Allah, da (dabbar) da ta shaƙe, da wadda aka doke ta, da wadda ta gangaro (daga sama), da dabbar da aka tunkura da ƙaho, da kuma abin da namun daji masu farauta suka ci, sai dai abin da kuka samu damar yankawa (daga cikinsu), da kuma abin da aka yanka a kan gumaka, da kuma neman sanin sa’a da kibau. Wannan fasiƙanci ne. A yau kafirai sun ɗebe tsammani daga (karya) addininku, don haka kar ku ji tsoron su, ku ji tsoro Na Ni kaɗai. A yau Na cika muku addininku, kuma Na cika muku ni’imata, kuma Na yardar muku Musulunci ya zamo shi ne addininku. Duk wanda ya matsu (ya ci abin da aka ambata a baya) saboda yunwa, ba yana mai karkata zuwa ga zunubi ba, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A wannan ayar Allah ya bayyana dabbobin da aka haramta cin su.

1. Allah ya haramta cin naman mushen dabba.

2. Ya haramta jini mai kwarara, kamar jinin dabbar da aka yanka, ko jinin da ya zubo saboda katsewar wata jijiya a jikinta.

3. Ya haramta cin naman dabbar da aka yanka ta da sunan wani ba Allah ba.

4. Ya haramta cin naman dabbar da aka shaƙe ta ta mutu, ko ita da kanta ta sa kanta cikin wani wuri ya shaƙe ta ta mutu.

5. Ya haramta cin dabbar da aka doke ta har ta mutu.

6. Ya haramta cin dabbar da ta gangaro daga wani wuri mai tudu, ko ta gangara cikin rami ta mutu.

7. Ya haramta cin dabbar da ‘yar’uwarta ta soke ta da ƙaho ta mutu.

8. Ya haramta cin naman dabbar da wani naman daji mai farauta ya fara ci ta mutu a sanadiyyar haka. Sai dai idan waɗannan dabbobi da aka ambata aka same su ba su mutu ba aka yanka su, yanka na shari’a, to waɗannan ya halatta a ci su.

9. Hakanan an haramta cin dabbar da aka yanka wa wani gunki ko kuma duk wani abin da ake bauta wa ba Allah ba.

An karɓo daga Adiyyu ɗan Hatim (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Na ce: “Ya Manzon Allah, ni nakan saki karnukan farauta sai su kamo mini abin farauta, to ko na iya ambaton Allah in ci?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan ka saki karen farautarka, kuma ka ambaci sunan Allah, to ka ci abin da ya kamo maka.” Sai na ce: “Ko da karnukan sun kashe dabbar?” Ya ce: “E, ko da sun kashe ta, matuƙar dai wani karen da ba a cikinsu yake ba bai yi tarayya da su ba.” [Muslim #1929].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin abubuwan da ya haramta wa muminai, kamar neman sa’a da kibau. Wannan wata al’ada ce ta Larabawa a lokacin jahiliyya, wato idan mutum ya nufi aikata wani abu, sai ya ɗauko kibau guda uku, ta ɗaya an rubuta a kanta: “Aikata”, ta biyu kuma an rubuta: “Kada ka aikata”, ta uku kuma babu komai a jikinta. Sai ya karkaɗa su ya juya, idan wadda take ɗauke da rubutun ‘aikata’ ta fito, sai ya aikata abin; idan kuma mai ɗauke da ‘kada ka aikata’ ta fito, sai ya fasa aikata abin; idan kuma ta ukun ce marar rubutu a jikinta ta fito, to sai ya sake kaɗawa ya jujjuya har sai ɗaya daga cikin biyu na farko ta fito. To shi ne Allah ya haramta musu wannan mummunar al’ada, domin ta ƙunshi jingina wa wanin Allah tasirin samar da amfani ko rashinsa ga mutum, wanda yin haka kuwa shirka ne ga Allah. Allah kuma ya kira waɗannan abubuwa da ya haramta duka a matsayin fasiƙanci, wato fita daga biyayya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zuwa ga saɓa masa.Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labari a ranar Arfa ta hajjin ban-kwana da Annabi (ﷺ) ya yi da sahabbansa cewa, kafirai sun fitar da rai da ganin Musulmi za su yi ridda su bar addininsu, don haka kada mumimai su riƙa jin tsoron su, su ji tsoron Allah shi kaɗai. Sai Allah ya bayyana cewa, daga wannan rana ta Arfa, ya cika wa muminai addininsu, ya cika musu ni’imarsa, ya yarje musu Musulunci a matsayin addinin da za su kusance shi da shi.Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dawo da batun waɗannan dabbobi da ya haramta cin su, ya bayyana cewa duk wanda ya shiga halin larura da matsuwa ta yadda sai ya ci wani abu daga cikin waɗannan dabbobi zai tsira da rayuwarsa ko lafiyarsa, to babu laifi ya ci gwargwadon abin da zai raba shi da wannan larurar, ba tare da ya yi nufin haramun ba. Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗayin sahabbai a kan neman ilimi.

2. Halattawa da haramtawa haƙƙin Allah ne shi kaɗai. Bai halatta ga wani mutum ba, komai matsayinsa, ya halatta ko ya haramta abin da ba shi da wani nassi a kansa. Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) yana bayanin halal da haram ne daga wahayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi masa, shi ya sa a nan ya ba shi umarni da “Ka ce....”

3. Duk abin da Allah ya halatta, to mai daɗi ne, kuma yana da amfani a jiki ko a zuciya ga mutum ɗaya, ko ga al’umma duka. Hakanan za mu fahimci cewa duk abin da ya haramta lalatacce ne, ba shi da wani amfani ga mutum.

4. Daga aya ta 5 za mu gane cewa, dukkan kyawawan abubuwa halal ne.

5. Halaccin ajiye karen farauta.

6. Falalar ilimi. Dubi yadda har a cikin dabbobi Allah ya fifita dabbar farautar da take da ilimi a kan wadda ba ta da ilimi, ya halatta a ci abin da ta kamo.

7. Yalwata wa bayi hanyoyin samun arziki.

8. Saukin addinin Musulunci wajen mu’amala da waɗanda ba Musulmi ba, waɗanda suke rayuwa a ƙasashen Musulmi, ko suke da wata yarjejeniya a tsakaninsu, daga cikin Yahudawa ko Nasara, ta yadda Musulunci ba ya ba su ‘yancin yin addininsu ne kaɗai ba, a’a, ya ma halatatta wa Musulmi su ci yankansu, su ma su ci yankan Musulmi, ya kuma halatta wa Musulmi auren matansu masu kame kai idan da buƙatar yin hakan.

9. Duk waɗanda suke ba Yahudawa ba, ba kuma Nasara ba, to bai halatta Musulmi ya ci yankansu ba.

10. Duk abin da mutum yake takama yana da shi na ilimi, to kada ya manta da cewa Allah ne ya sanar da shi wannan ilimin, don haka wajibi ne ya yi tawali’u, ya guji girman kai.

Suratul Ma’ida (4-5)

يَسْـَٔلُونَكَ مَاذَآ أُحِلَّ لَهُمْۖ قُلْ أُحِلَّ لَكُمُ ٱلطَّيِّبَٰتُ وَمَا عَلَّمْتُم مِّنَ ٱلْجَوَارِحِ مُكَلِّبِينَ تُعَلِّمُونَهُنَّ مِمَّا عَلَّمَكُمُ ٱللَّهُۖ فَكُلُواْ مِمَّآ أَمْسَكْنَ عَلَيْكُمْ وَٱذْكُرُواْ ٱسْمَ ٱللَّهِ عَلَيْهِۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ۝٤ ٱلْيَوْمَ أُحِلَّ لَكُمُ ٱلطَّيِّبَٰتُۖ وَطَعَامُ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلْكِتَٰبَ حِلٌّ لَّكُمْ وَطَعَامُكُمْ حِلٌّ لَّهُمْۖ وَٱلْمُحْصَنَٰتُ مِنَ ٱلْمُؤْمِنَٰتِ وَٱلْمُحْصَنَٰتُ مِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلْكِتَٰبَ مِن قَبْلِكُمْ إِذَآ ءَاتَيْتُمُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ مُحْصِنِينَ غَيْرَ مُسَٰفِحِينَ وَلَا مُتَّخِذِيٓ أَخْدَانٍۗ وَمَن يَكْفُرْ بِٱلْإِيمَٰنِ فَقَدْ حَبِطَ عَمَلُهُۥ وَهُوَ فِى ٱلْءَاخِرَةِ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ۝٥

4. Suna tambayar ka, mene ne aka halatta musu? Ka ce: “An halatta muku kyawawan abubuwa da kuma abin da dabbobinku da kuka koyar da su (farauta) suka kamo muku, kuna koya musu abin da Allah Ya koya muku, don haka ku ci daga duk abin da suka kamo muku, sannan ku ambaci sunan Allah a kansa; kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai gaggawar hisabi ne.

5. A yau an halatta muku kyawawan abubuwa; kuma abincin waɗanda aka bai wa Littafi halal ne a gare ku, ku ma abincinku halal ne a gare su; sannan kuma (na halatta muku auren) mata kamammu daga cikin muminai, da kuma kamammu daga cikin waɗanda aka bai wa Littafi a gabaninku, idan har kun ba su sadakinsu, kuna masu kame kawunanku, ba kuna mazinata ba, ba kuma kuna masu yin daduro ba. Duk kuwa wanda ya kafirce wa imani, haƙiƙa aikinsa ya rushe, kuma a ranar lahira yana cikin asararru.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, sahabbansa suna yi masa tambaya game da abubuwan ci da aka halatta musu. Sannan ya umarce shi da ya ba su amsa da cewa, Allah ya halatta musu cin kyawawan abubuwa, wato su ci duk abin da yake mai amfani ga ɗan’adam, kuma ba zai cutar da jikinsa ko hankalinsa ba. Hakanan ya halatta musu cin abin da dabbobinsu na farauta waɗanda suka koyar da su farauta suka kamo. Su koyar da su abin da Allah ya koya musu na ladubban farauta da ƙa’idojinta, su ci abin da waɗannan dabbobin suka kamo musu, kuma su riƙa ambaton sunan Allah yayin da za su sake su farautar. Su ji tsoron Allah ta hanyar kula da aiki da waɗannan hukunce-hukunce da aka sanar da su, su sani cewa Allah mai gaggawar hisabi ne.

An karɓo daga Adiyyu ɗan Hatim (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Ya Manzon Allah, nakan saki karen farautata, kuma in yi *Bisimilla*.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan ka saki karenka, kuma ka yi *Bisimilla*, sai ya kamo abin farauta ya kashe ya fara ci, to kada ka ci, domin kansa ya kamo wa.” Sai na ce: “Ya Manzon Allah, nakan saki karen farautata, to amma sai in same shi tare da wani kare, to sai in kasa ganewa cikinsu wane ne ya kama abin farautar.” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Kada ka ci, domin karenka ka yi wa *Bisimilla* ba wani ba.” [Bukhari #5486, da Muslim #1929].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da kawo wasu alamomi na cikar addinin Musulunci, da kuma wasu ni'imominsa da sauƙin da ke tattare da wannan addini. Daga cikinsu, ya halatta wa muminai su more duk wasu kyawawan abubuwa na abinci da abin sha, kuma ya halatta musu cin yankan ma'abota littafi, wato Yahudu da Nasara, ya kuma halatta musu su auri mata 'ya'ya, muminai, kamammu da kamammun matan Yahudawa da Nasara idan sun biya sadakinsu, su mazajen kuma suna kamammu ba mazinata ba, ba kuma masu ajiye dadiro ba suna zina da su a ɓoye. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya kafirce masa, to ladan ayyukansa masu kyau ya rushe idan har ya mutu bai tuba ba, a lahira kuma ya sami kansa cikin hasararru, waɗanda suka yi hasarar kawunansu da dukiyoyinsu da iyalansu, suka cancanci azaba ta har abada.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga yin tunani game da ni'imomin Allah.

2. Wajibi ne mutum ya riƙa tuna alƙawarin da ya ɗauka tsakaninsa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) na cewa, zai ji kuma zai yi biyayya.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce mu da mu riƙa tuna ni'imominsa. Ba kuma mu tuna su mu ba da labarinsu kaɗai ba, a'a, mu yi masa godiya a kansu.

4. Razanarwa ga marar tsoron Allah. Tsoron Allah kuma yana samo asali ne daga zuciya, sannan ya yi naso a kan gaɓoɓi.

5. Wajabcin bayar da shaida don Allah.

6. Haramcin ɓoye shaida ko da kuwa za ta cutar da shi ko wani nasa.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci kowa da kowa a kan bayar da shaida ta gaskiya da adalci da kauce wa zalunci da son kai.

8. Ya wajaba a kan mumini ya zamanto mai kai zuciya nesa, mai gaskiya wajen mu'amala da mutane ko da kuwa maƙiyansa ne.

9. Imani ba ya cika sai tare da ayyuka na ƙwarai.

10. Wajabcin dogaro ga Allah, domin yana daga cikin imani da Allah.

Suratul Ma'ida (6)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا قُمْتُمْ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ فَٱغْسِلُواْ وُجُوهَكُمْ وَأَيْدِيَكُمْ إِلَى ٱلْمَرَافِقِ وَٱمْسَحُواْ بِرُءُوسِكُمْ وَأَرْجُلَكُمْ إِلَى ٱلْكَعْبَيْنِ ۚ وَإِن كُنتُمْ جُنُبًا فَٱطَّهَّرُواْ ۚ وَإِن كُنتُم مَّرْضَىٰٓ أَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ أَوْ جَآءَ أَحَدٌ مِّنكُم مِّنَ ٱلْغَآئِطِ أَوْ لَـٰمَسْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَلَمْ تَجِدُواْ مَآءً فَتَيَمَّمُواْ صَعِيدًا طَيِّبًا فَٱمْسَحُواْ بِوُجُوهِكُمْ وَأَيْدِيكُم مِّنْهُ ۚ مَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيَجْعَلَ عَلَيْكُم مِّنْ حَرَجٍ وَلَـٰكِن يُرِيدُ لِيُطَهِّرَكُمْ وَلِيُتِمَّ نِعْمَتَهُۥ عَلَيْكُمْ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ٦

6. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kun tashi za ku yi salla, to ku wanke fuskokinku da hannayenku zuwa gwiwoyinsu, kuma ku shafi kawunanku, kuma (ku wanke) ƙafafunku zuwa idon sawu. Kuma idan

kun kasance masu janaba, to sai ku tsarkaka. Idan kuma kun kasance marasa lafiya, ko a halin tafiya, ko ɗaya daga cikinku ya dawo daga bayan gari, ko kuka sadu da mata, kuma sai ba ku sami ruwa ba, to ku yi taimama a doron ƙasa mai tsarki, ku shafi fuskokinku da hannayenku daga shi. Allah ba Yana nufin Ya sanya ƙunci a tare da ku ba ne, a'a, Yana nufi ne Ya tsarkake ku, kuma Ya cika ni'imarsa a gare ku, don ku zamo masu godiya.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da muminai wani babban alƙawari ne da ke tsakaninsu da shi, da yadda ya wajaba su kiyaye shi, watau al'amarin salla. Allah ya bayyana abin da yake wajaba a kan mumini ya yi yayin da ya tashi domin sauke nauyin alƙawarin salla da ke kansa, ya umarce shi da yin alwala watau ya wanke fuska da hannaye zuwa gwiwowinsu da shafar kai da wanke ƙafafuwa ko shafar su idan yana sanye da takalmin huffi. Sannan ya bayyana hukuncin wanda yake da janaba a jikinsa, shi kuma sai ya yi wankan janaba. Idan kuwa mutum yana rashin lafiyar da ba zai iya taɓa ruwa ba, ko yana cikin halin tafiya, ko ya sami ƙaramin kari, kamar bawali ko bahaya, ko kuma ya sadu da matarsa, duk waɗannan yayin da suka rasa ruwan da za su yi amfani da shi wajen yin alwala ko wanka, to sai su nemi doron ƙasa mai tsarki su yi taimama a kai, su shafi fuskokinsu da tafukan hannayensu. Allah ba ya nufin ya jefa bayinsa cikin ƙunci da takura; yana nufin tsarkake su ne da abin da ya farlanta musu na alwala da wanka da taimama, sannan yana son ya tsarkake musu baɗininsu ta hanyar kankare musu laifukansu, kuma ya cika musu ni'imarsa ta hanyar cika musu shari'o'insa da sassauta musu hukunce-hukuncensa, ko wataƙila sa yi wa Allah godiya a kan hakan da zukatansu da harsunansu da gaɓoɓinsu.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga yin tunani game da ni'imomin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Wajibi ne kowane mutum ya riƙa tuna alƙawarin da ke tsakaninsa da Allah na zai saurari umarninsa, kuma zai bi shi. Kuma sauraro shi kaɗai ba tare da biyayya ba, ba shi da wani amfani ga bawa.

3. Ana tuna ni'imomin Allah ne domin a gode masa a kansu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kare bawansa daga wani sharri ko ya tsare shi daga masu yi masa mugun nufi, wata ni'ima ce da ta wajaba bawa ya yi wa Allah godiya a kanta.

5. Gargaɗin duk wanda ba ya jin tsoron Allah da cewa Allah yana sane da duk abin da yake cikin zukata. Wannan yana nuna cewa taƙawa dole ne a gina ta a kan gyaran zukata, ba kawai maganganun baka ba.

6. Allah ya yi ta nanata maganar taƙawa domin ya nuna cewa, gaba ɗayan Musulunci ya ginu ne a kanta. Duk sa'adda bawa ya zama mai kiyaye dokokin Allah, to zai zama mai riƙo da addininsa da aiki da koyarwarsa.

7. Wajabcin yin ikhlasi a cikin shaida, wato ya bayar da ita don Allah, ba tare da la'akari da 'yan'uwantaka ko soyayya ko ƙiyayya ba.

8. Yin shaida da adalci ko mutum ba ya so, domin akwai wanda zai ɓoye shaidar da ya sani don yana ganin bayyana ta zai cutar da wani masoyinsa.

9. Nuni a kan yi wa mutane mu'amala a bisa mizanin adalci cikin duk wani abu na rayuwa ta zamantakewa, ba tare da nuna bambanci ba a tsakanin abokan mu'amala ko abokan zama.

10. Imani da fatar baki kaɗai ba zai wadatar ba, dole ne sai ya haɗu da kyawawan ayyuka sannan ne yake zama mai amfani a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

11. Wajibi ne ga bawa ya zama mai dogara da Allah shi kaɗai cikin dukkan lamuransa na addini da na rayuwa.

Suratul Ma'ida (7-11)

وَٱذۡكُرُواْ نِعۡمَةَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَمِيثَٰقَهُ ٱلَّذِي وَاثَقَكُم بِهِۦٓ إِذۡ قُلۡتُمۡ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ لِلَّهِ شُهَدَآءَ بِٱلۡقِسۡطِۖ وَلَا يَجۡرِمَنَّكُمۡ شَنَـَٔانُ قَوۡمٍ عَلَىٰٓ أَلَّا تَعۡدِلُواْۚ ٱعۡدِلُواْ هُوَ أَقۡرَبُ لِلتَّقۡوَىٰۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ٨ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٌ عَظِيمٞ ٩ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ١٠ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ إِذۡ هَمَّ قَوۡمٌ أَن يَبۡسُطُوٓاْ إِلَيۡكُمۡ أَيۡدِيَهُمۡ فَكَفَّ أَيۡدِيَهُمۡ عَنكُمۡۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١١

7. Kuma ku tuna ni'imar Allah da Ya yi muku, da alƙawarinsa wanda Ya ƙulla shi da ku, yayin da kuka ce: "Mun ji, kuma za mu yi biyayya!" Kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Masanin abin da ƙiraza suka ƙunsa ne.

8. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku zamo masu tsayawa ƙyam da haƙƙokin Allah, kuna masu yin shaida da adalci; kuma kada ƙin waɗansu mutane ya hana ku yi musu adalci. Ku yi adalci shi ne mafi kusanci ga taƙawa. Kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne.

9. Allah Ya yi alƙawari ga waɗanda suka yi imani, kuma suka yi aiki nagari, suna da gafara da kuma lada mai girma.

10. Kuma waɗanda suka kafirta, suka kuma ƙaryata ayoyinmu, waɗannan su ne 'yan wuta.

11. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku tuna ni'imar Allah da Ya yi muku, yayin da waɗansu mutane suka yi niyyar shimfiɗa hannayensu a kanku, sai Ya kame muku hannayensu, kuma ku kiyaye dokokin Allah. To sai muminai su dogara ga Allah Shi kaɗai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tuna wa muminai ni'imar da ya yi musu da alƙawarin da ya yi da su na za su yi wa Annabi (ﷺ) mubaya'a, za su taimaka masa a kan yaɗa addinin Allah, kuma suka yarda da wannan alƙawari a wannan lokaci, suka ce: "Mun ji, kuma mun bi." Sannan ya umarce su da jin tsoron sa, domin shi masanin abin da yake cikin zukata ne.
Sai kuma ya umarci muminai da su kiyaye haƙƙokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), suna masu ikhlasi cikin duk ayyukansu. Hakanan su zama masu adalci lokacin da suke bayar da shaida, kada kuma ƙin wani ko wasu ya hana su yi musu adalci, a'a, su zama masu adalci koyaushe, domin yin haka shi zai wanzar musu da cikakken tsoron Allah a zukatansu. Don haka su kiyaye dokokin Allah, domin shi mai cikakken sanin abin da suke aikatawa ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya yi wa muminai masu aikata kyawawan ayyuka alƙawarin gafarar zunubansu da samun wani lada mai girma, wanda shi ne Aljanna. To amma waɗanda suka kafirce masa, kuma suka ƙaryata ayoyinsa, su ne 'yan wuta masu dawwama a cikinta har abada.

Sannan ya ƙara jan hankalin muminai su riƙa tuna ni’imomin da ya yi musu lokacin da wasu maƙiyansu suka ƙuduri aniyar auka musu, amma sai ya kare su daga sharrinsu, ya hana musu samun biyan mummunar buƙatarsu a kan muminai. Sai kuma ya rufe ayar da umarnin a ji tsoron sa ta hanyar kiyaye dokokinsa, sannan muminai su dogara da shi shi kaɗai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ya kamata kowace ƙungiya ta mutane da za su haɗu a sami shugaba daga cikinsu wanda za a saurare shi duk sa’adda aka sami wani saɓani.

2. Wajibi ne mumini ya tsayar da salla tare da kula da rukunanta da wajibanta da sunnoninta domin ta zama mai tasiri a zuciya da gangar jiki ta sadar da bawa da tarbiyya ta Ubangijinsa.

3. A tare da bayar da zakka akwai iƙirarin bawa da ni’imar da Allah ya yi masa da yarda da cewa dukiyar da take hannunsa mallakar mahaliccinsa ce, wanda hakan zai ƙara masa sha’awar fitar da ita wajen ginin al’umma a bisa tsarin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Wajabcin taimaka wa manzannin Allah lokacin rayuwarsu ta hanyar fita tare da su yaƙi, da kuma bayan rasuwarsu ta hanyar yaɗa karantarwarsu da koyar da shari’arsu ga mutane.

5. Zuciya tana ƙeƙashewa saboda yawan saɓon Allah da mai ita yake ta yi. Haka kuma idan bawa yana biyayya ga Allah da Manzonsa, to zuciyarsa za ta natsu ta yi laushi. Don haka maganin ƙeƙashewar zuciya shi ne bin Allah da Manzonsa da ambaton Allah Ta’ala.

6. Yawan saɓa wa Allah yana dusashe fahimtar maganar Allah, ko ma ya hana fahimtar gaba ɗaya.

7. Keƙashewar zuciya da canza maganar Allah da watsi da wa’azi duk suna daga cikin halayen Yahudawa, don haka duk wanda ya sifantu da irin waɗannan halaye, to ya siffantu da halayen Yahudawa.

8. Musulunci addini ne mai kyakkyawar mu’amala da maƙiyansa, don haka yake umarni da a yi musu afuwa, a kawar da kai daga kansu bayan an ci nasara a kansu.

9. Tozarta haƙƙin Allah da Manzonsa na daga cikin abubuwan da suke haifar da gaba da ƙiyayya a tsakanin mutane, kamar yadda biyayya ga Allah da Manzonsa da riƙe addininsa suke kawo ƙauna da taimakon juna tsakanin mutane.

Suratul Ma’ida (12-14)

*وَلَقَدۡ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ وَبَعَثۡنَا مِنۡهُمُ ٱثۡنَيۡ عَشَرَ نَقِيبٗاۖ وَقَالَ ٱللَّهُ إِنِّي مَعَكُمۡۖ لَئِنۡ أَقَمۡتُمُ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَيۡتُمُ ٱلزَّكَوٰةَ وَءَامَنتُم بِرُسُلِي وَعَزَّرۡتُمُوهُمۡ وَأَقۡرَضۡتُمُ ٱللَّهَ قَرۡضًا حَسَنٗا لَّأُكَفِّرَنَّ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَلَأُدۡخِلَنَّكُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۚ فَمَن كَفَرَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ مِنكُمۡ فَقَدۡ ضَلَّ سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ١٢ فَبِمَا نَقۡضِهِم مِّيثَٰقَهُمۡ لَعَنَّٰهُمۡ وَجَعَلۡنَا قُلُوبَهُمۡ قَٰسِيَةٗۖ يُحَرِّفُونَ ٱلۡكَلِمَ عَن مَّوَاضِعِهِۦ وَنَسُواْ حَظّٗا مِّمَّا ذُكِّرُواْ بِهِۦۚ وَلَا تَزَالُ تَطَّلِعُ عَلَىٰ خَآئِنَةٖ مِّنۡهُمۡ إِلَّا قَلِيلٗا مِّنۡهُمۡۖ فَٱعۡفُ عَنۡهُمۡ وَٱصۡفَحۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٣ وَمِنَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّا نَصَٰرَىٰٓ أَخَذۡنَا مِيثَٰقَهُمۡ فَنَسُواْ حَظّٗا مِّمَّا ذُكِّرُواْ بِهِۦ فَأَغۡرَيۡنَا بَيۡنَهُمُ ٱلۡعَدَٰوَةَ وَٱلۡبَغۡضَآءَ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ وَسَوۡفَ يُنَبِّئُهُمُ ٱللَّهُ بِمَا كَانُواْ يَصۡنَعُونَ ١٤

12. Kuma lalle haƙiƙa Allah Ya ɗauki alƙawari (daga) Banu-Isra'ila, kuma Mun aiko musu wakilai goma sha biyu daga cikinsu; kuma Allah Ya ce: "Lalle Ni Ina tare da ku; tabbas idan har kuka tsayar da salla, kuma kuka bayar da zakka, kuma kuka yi imani da manzannina, kuma kuka ƙarfafe su, kuma kuka bai wa Allah kyakkyawan rance, to lalle zan kankare muku kurakuranku, kuma zan shigar da ku gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. To duk wanda ya kafirce daga cikinku bayan haka, to haƙiƙa ya ɓace wa tafarki madaidaici."

13. Saboda yadda suke warware alƙawarin da aka yi da su, sai Muka la'ance su, kuma Muka sanya zukatansu suka zamo ƙeƙasassu; suna jirkita magana daga wurinta, kuma sun bar wani rabo na abin da aka yi musu wa'azi da shi. Kuma ba za ka gushe ba kana ganin ha'inci daga gare su, sai 'yan kaɗan daga cikinsu. To sai ka yi musu afuwa, kuma ka kawar da kai, lalle Allah Yana son masu kyautatawa.

14. Kuma daga cikin waɗanda suka ce: "Lalle mu Nasara ne," su ma Mun riƙi alƙawarinsu, sai suka bar wani kaso na abin da aka yi musu wa'azi da shi, sai Muka iza wutar gaba da ƙiyayya a tsakaninsu har zuwa ranar tashin alƙiyama. Kuma da sannu Allah zai ba su labarin abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin cewa, ya ɗauki wani alƙawari mai ƙarfi tare da Yahudawan da suka gabata. Kuma ya naɗa musu shugabanni goma sha biyu daidai adadin gidajen Banu Isra'ila, kuma ya umarci ƙowane shugaba da cewa, mutanen da suke ƙarƙashinsa su yi masa mubaya'a a kan cewa, za su saurari duk abin da aka faɗa musu, kuma za su yi biyayya tare da cika alƙawarin da suka ɗauka, shi kuma ya sa musu ido a kan haka.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya faɗa wa Banu Isra'ila cewa yana tare da su da taimakonsa da nasararsa, matuƙar za su cika alƙawarin da suka yi da shi, ta hanyar tsayar da salla kamar yadda ya kamata, kuma su ba da zakkar dukiyoyinsu ga waɗanda suka cancanta a ba, kuma su yi imani da manzannin Allah da taimaka musu a kan maƙiyansu, da ciyar da dukiyoyinsu don neman yardar Allah. Idan sun yi duk waɗannan abubuwa da aka ambata, to Allah zai yafe musu zunubbansu, kuma zai shigar da su gidajen Aljanna, waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. To amma kuma duk wanda ya kafirce, ya karya alƙawarin da ya ɗauka, to haƙiƙa ya ɓace wa hanya madaidaiciya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuma bayyana cewa, a dalilin rashin cika alƙawarinsu ne ya la'ance su, ya sanya zukatansu suka ƙeƙashe har wa'azi ba ya yi musu tasiri, alheri ba ya ratsa su, suka riƙa canza maganar Allah a Attaura, kuma suka yi watsi da mafi yawan abin da aka yi musu wahayin sa na faɗakarwa da tunatarwa da gangan. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, ba zai gushe ba yana bankaɗo makirce-makircen Yahudawa da cin amanarsu da yaudararsu, sai 'yan kaɗan daga cikinsu ne za a same su suna cika alƙawari idan sun ɗauka. Sannan Allah ya umarce shi da ya yi musu afuwar laifukansu, kuma ya kawar musu da kai, Allah yana son masu kyautatawa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya ɗauki alƙawari mai ƙarfi da mutanen da suka cika bakin cewa, wai su Nasara ne, ya umarce su da cewa, su yi wa Allah da manzanninsa biyayya, amma kuma sai suka yi watsi da abin da ake yi musu wa'azi da shi na wahayin Allah da gangan, sai Allah ya yi musu uƙuba ta hanyar sanya ƙiyayya da saɓani a tsakaninsu, suna faɗa da juna, suna kafirta juna, suna la'antar juna har zuwa ranar tashin ƙiyama. Kuma Allah zai ba su labarin duk abin da suka aikata a nan duniya, kuma zai yi musu azaba a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi (ﷺ) Manzo ne na Allah zuwa ga ɗaukacin mutanen duniya gaba ɗaya har da Yahudawa da Nasara.

2. Bayanin addinin Allah da fito da gaskiyar da take cikinsa, ba zai dakata ba har ƙarshen rayuwa. Duk sa'adda wata sunna ta ɓace, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fito da wani malami wanda zai mayar da mutane kanta.

3. Yahudawa da Nasara masu ɓoye ilimi ne, don haka duk wanda yake ɓoye ilimi daga cikin wannan al'umma, to ya yi kama da su.

4. Duk wanda ya bi abin da Allah ya yarda da shi, to fahimtarsa da shari'ar Allah za ta ƙaru, kamar yadda duk wanda ya bijire wa hanyar Allah, to ba zai taɓa fahimtar shiriya ba.

5. Wanda duk ya bi shari'ar Allah, to shi kam ya kuɓuta gaba ɗaya. Ya kuɓuta a aƙidarsa, da ibadarsa, da mu'amalarsa, ya kama hanyar zuwa gidan aminci, shi ne Aljanna.

6. Musulunci addini ne na aminci a rayuwa gaba ɗaya: A rayuwar mutum shi kaɗai da rayuwar al'umma da rayuwar duniya gaba ɗayanta. Kauce masa da watsi da karantarwarsa shi ne yake jefa al'umma cikin tashin hankali da rashin samun nutsuwa da walwala ta rayuwa.

7. Duk wani tsari da ya saba wa Musulunci duhu ne, tatsuniya ce, son zuciya ne, ƙarya ce, kuma zalunci ne.

8. Duk sa'adda ɗan'adam ya yi riƙo da shari'ar Allah, to Allah zai shiryar da shi.9. Shari'ar Musulunci haske ne a rayuwar ɗan'adam.

Suratul Ma'ida (15-16)

يَـٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ قَدۡ جَآءَكُمۡ رَسُولُنَا يُبَيِّنُ لَكُمۡ كَثِيرٗا مِّمَّا كُنتُمۡ تُخۡفُونَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَيَعۡفُواْ عَن كَثِيرٖۚ قَدۡ جَآءَكُم مِّنَ ٱللَّهِ نُورٞ وَكِتَٰبٞ مُّبِينٞ ١٥ يَهۡدِي بِهِ ٱللَّهُ مَنِ ٱتَّبَعَ رِضۡوَٰنَهُۥ سُبُلَ ٱلسَّلَٰمِ وَيُخۡرِجُهُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ بِإِذۡنِهِۦ وَيَهۡدِيهِمۡ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ١٦

15. Ya ku waɗanda aka bai wa Littafi, haƙiƙa Manzonmu ya zo muku, yana bayyana muku da yawa daga cikin abin da kuke ɓoyewa daga Littafin, yana kuma yin afuwa ga abubuwa da dama daga ciki. Haƙiƙa haske ya zo muku daga Allah, da kuma Littafi mai bayyanawa.

16. Da shi ne Allah Yake shiryar da wanda ya bi yardarsa hanyoyi na aminci, kuma Yake fitar da su daga duffai zuwa ga haske da izininsa, kuma Yana shiryar da su zuwa ga tafarki madaidaici.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Yahudawa da Nasara cewa, ya aiko musu da Manzonsa Muhammadu (ﷺ) wanda da man sun riga sun karanci siffofinsa a cikin littattafansu, zai zo ya riƙa bayyana wasu hukunce-hukunce masu yawa da suke ɓoye wa mutane, kamar hukuncin jefe mazinacin da ya taɓa yin aure, da kuma canza maganar Allah, kuma zai bar wasu abubuwan waɗanda babu wani amfani don ya bayyana su. Sannan ya tunatar da su cewa wani Littafi babba daga Allah ya zo musu, watau Alƙur'ani mai girma, wanda yake haske ne da yake haskaka duffai na jahilci da ɓata, yana yi wa mutane bayanin duk abin da suke buƙata su sani na hukunce-hukuncen addininsu da rayuwarsu. Da shi ne yake nuna hanya ga duk wanda yake son isa ga yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sai ya datar da su wajen bin hanyar tsira a duniya da lahira da samun shiga Aljanna gidan aminci. Kuma da shi yake fitar da su daga duffai na ɓata da kafirci da saɓon Allah, zuwa ga hasken imani da biyayya ga Allah da Manzonsa da izinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma ya shiryar da su zuwa ga daidaitacciyar hanya wadda ita ce Musulunci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nasara masu aƙidar cewa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ɗan Allah ne su kafirai ne.

2. Ya halatta a kira mutum da sunan mahaifiyarsa idan ba a san mahaifinsa ba.3. Idan Allah ya nufi aikata wani abu, to babu wani mai daraja ko dukiya ko mulkin da ya isa ya hana Allah zartar da nufinsa.

4. Annabi (ﷺ) an aiko shi ne don ya isar da saƙon da aka aiko shi da shi, kuma ya isar.

5. Muhimmancin koyon wani baƙon harshe don bayyana wa masu wannan harshe saƙon da Annabi (ﷺ) ya zo da shi, yin haka babban aikin lada ne, domin siffa ce daga cikin siffofin Annabi (ﷺ) cewa, yana yi wa mutane bayanin addinin Allah.

Suratul Ma'ida (17-19)

لَّقَدْ كَفَرَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْمَسِيحُ ٱبْنُ مَرْيَمَۚ قُلْ فَمَن يَمْلِكُ مِنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا إِنْ أَرَادَ أَن يُهْلِكَ ٱلْمَسِيحَ ٱبْنَ مَرْيَمَ وَأُمَّهُۥ وَمَن فِى ٱلْأَرْضِ جَمِيعًاۗ وَلِلَّهِ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَاۚ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٧﴾ وَقَالَتِ ٱلْيَهُودُ وَٱلنَّصَٰرَىٰ نَحْنُ أَبْنَٰٓؤُاْ ٱللَّهِ وَأَحِبَّٰٓؤُهُۥۚ قُلْ فَلِمَ يُعَذِّبُكُم بِذُنُوبِكُمۖ بَلْ أَنتُم بَشَرٌ مِّمَّنْ خَلَقَۚ يَغْفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُۚ وَلِلَّهِ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَاۖ وَإِلَيْهِ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٨﴾ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ قَدْ جَآءَكُمْ رَسُولُنَا يُبَيِّنُ لَكُمْ عَلَىٰ فَتْرَةٍ مِّنَ ٱلرُّسُلِ أَن تَقُولُواْ مَا جَآءَنَا مِنۢ بَشِيرٍ وَلَا نَذِيرٍۖ فَقَدْ جَآءَكُم بَشِيرٌ وَنَذِيرٌۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٩﴾

17. Lalle haƙiƙa, waɗannan da suka ce: "Lalle Allah Shi ne Almasihu ɗan Maryamu" sun kafirta. Ka ce: "To wane ne ya isa ya hana Allah, idan Ya yi nufin Ya hallaka Almasihu ɗan Maryamu da mahaifiyarsa da duk wanda yake ban ƙasa gaba ɗaya? Allah kuwa Shi Yake mallakar abin da yake cikin sammai da ƙasa da kuma abin da yake tsakaninsu. Yana halittar abin da Ya ga dama. Kuma Allah Mai cikakken iko ne a kan komai."

18. Kuma Yahudawa da Nasara suka ce: "Mu 'ya'yan Allah ne, kuma masoyansa." Ka ce: "To don me Yake muku azaba a sanadiyyar zunubanku? Ba haka ne ba, ku mutane ne daga cikin waɗanda Ya halitta. Yana yin gafara ga wanda Ya ga dama, kuma Yana yin azaba ga wanda Ya ga dama. Kuma mulkin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu na Allah ne, kuma zuwa gare Shi ne makoma take."

19. Ya ku waɗanda aka bai wa Littafi, haƙiƙa Manzonmu ya zo muku, yana yi muku bayani bayan yankewar manzanci, don kar ku ce: "Ba wani mai bushara da ya zo mana, ko wani mai gargaɗi." To haƙiƙa mai busharar, kuma mai gargaɗin, ya zo muku. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rantsuwa a kan cewa Nasara masu cewa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ne sun kafirta. Kuma ya umarci Annabinsa (ﷺ) da ya faɗa musu cewa, idan ma Allah ya nufi halakar da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifiyarsa da mutanen duniya gaba ɗaya, wane ne ya isa ya hana shi? Babu wanda zai iya hana Allah ya zartar da duk abin da ya ga dama domin gaba ɗayansu suna ƙarƙashin ikonsa da mulkinsa. Wannan shi ya tabbatar da cewa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifiyarsa ba alloli ne ba, su ma kamar kowa suke, halittu ne na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Kuma mulkin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu duk na Allah ne, kuma shi mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gagarar sa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata katoɓara ta Yahudawa da Nasara ta cewa wai su ‘ya’yan Allah ne kuma su kaɗai ne masoyansa. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa (ﷺ) da ya ƙalubalance su da cewa, idan har maganar da suke faɗa gaskiya ce, to me ya sa Allah yake azabtar da su a kan laifukansu? Maganar dai ba haka take ba, su dai mutane ne kamar kowa, halittar su Allah ya yi kamar yadda ya halicci kowa da komai; yana kuma gafarta wa wanda ya ga dama, ya azabtar da wanda ya ga dama, don haka su ma irin wannan mu’amalar yake yi musu. Mulkin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu kuma duk nasa ne, kuma makoma gaba ɗaya zuwa gare shi ne.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Yahudawa da Nasara cewa ya aiko musu da Manzonsa (ﷺ), yana nuna musu miƙaƙƙiyar hanya da addinin gaskiya a lokacin da ake cikin matsananciyar buƙatar zuwansa saboda yankewar manzanni tun bayan Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya aiko shi don ya yanke hanzarin kowa a gaban Allah, don kada su zo suna cewa, su fa babu wani manzo mai albishir ko mai gargaɗi da ya zo musu. To ga shi dai mai albishir kuma mai gargaɗi ya zo musu, wanda shi ne Annabi Muhammadu (ﷺ). Kuma Allah mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi, don haka halittar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya yi ba uba sai uwa, idan ya ga dama zai iya halaka shi tare da mahaifiyarsa da mutanen duniya gaba ɗaya, ba wanda ya isa ya hana shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda Allah ya ba shi ilimi, to ya ba shi wata babbar ni’ima da ya wajaba a kansa ya riƙa tunawa da ita a koyaushe.

2. Matsayin malamai yana gaba da matsayin masu mulki, domin malamai su ne magada annabawa.

3. Ya kamata a riƙa tunatar da mutum ni’imar da Allah ya keɓance shi da ita.

4. Imani sharaɗi ne na tsantsanta dogaro ga Allah, domin babu mai dogaro da Allah yadda ya kamata sai mutumin da ya yi imani da alƙawarin Ubangiji.

5. Yana da kyau ga mai wa’azi ya riƙa ambaton sakamakon munanan laifuka, don tsoratarwa.

6. Dogaro ga Allah yana daga cikin hanyoyin samun nasara a kan abokan gaba.

7. Halaccin mutum ya roƙi Allah ya shiga tsakaninsa da fasiƙan mutane marasa tsoron Allah.

8. Nusar da mumini a kan cewa, kada ya riƙa damuwa da irin uƙubar da Allah yake yi wa masu laifi.

9. Samuwar malami a cikin al’umma ba ƙaramar ni’ima ba ce ga wannan al’umma.

10. Annabi Musa yana girmama Banu Isra’ila ta hanyar kiran su da: “Ya ku mutanena,” su kuma suna kiran sa da tsurar sunansa: “Ya Musa,” don wulaƙanci.

11. Mummunan zaton Banu Isra’ila ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

12. Fifikon matsayin sahabban Annabi (ﷺ) a kan mutanen Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Mutanen Annabi Musa sun ce masa: “Je ka kai da Ubangijinka ku yi yaƙin, lalle mu muna nan zaune,” amma sahabban Manzon Allah (ﷺ) ba haka suka faɗa masa ba. Lokacin da Annabi (ﷺ) ya fita yaƙin Badar da sahabbansa (Allah ya kara masa yarda), ya nemi shawararsu game da yaƙin, sai suka ce

masa: “Da za ka nemi mu faɗa tare da kai wannan tekun, da lalle za mu faɗa. Da za ka tafi da mu *Barkul Ghimad* (sunan wuri ne a Yemen), da tabbas mun bi ka gaba ɗayanmu; ba za mu faɗa maka irin abin da mutanen Annabi Musa suka faɗa masa ba cewa: “Je ka kai da Ubangijinka ku yi yaƙin, lalle mu muna nan a zaune.” Sai dai mu mu faɗa maka cewa, ka je kai da Ubangijinka ku yi yaƙin, kuma mu ma mayaƙa ne tare da ku, a gabanka da bayanka da damarka da hauninka.” [Muslim #1779, Hadisin Anas, da Bukhari #3952, Hadisin Ibn Mas’ud].

Suratul Ma’ida (20-26)

وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ يَٰقَوْمِ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَةَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ إِذْ جَعَلَ فِيكُمْ أَنۢبِيَآءَ وَجَعَلَكُم مُّلُوكًا وَءَاتَىٰكُم مَّا لَمْ يُؤْتِ أَحَدًا مِّنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٠﴾ يَٰقَوْمِ ٱدْخُلُوا۟ ٱلْأَرْضَ ٱلْمُقَدَّسَةَ ٱلَّتِى كَتَبَ ٱللَّهُ لَكُمْ وَلَا تَرْتَدُّوا۟ عَلَىٰٓ أَدْبَٰرِكُمْ فَتَنقَلِبُوا۟ خَٰسِرِينَ ﴿٢١﴾ قَالُوا۟ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّ فِيهَا قَوْمًا جَبَّارِينَ وَإِنَّا لَن نَّدْخُلَهَا حَتَّىٰ يَخْرُجُوا۟ مِنْهَا فَإِن يَخْرُجُوا۟ مِنْهَا فَإِنَّا دَٰخِلُونَ ﴿٢٢﴾ قَالَ رَجُلَانِ مِنَ ٱلَّذِينَ يَخَافُونَ أَنْعَمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمَا ٱدْخُلُوا۟ عَلَيْهِمُ ٱلْبَابَ فَإِذَا دَخَلْتُمُوهُ فَإِنَّكُمْ غَٰلِبُونَ ۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَتَوَكَّلُوٓا۟ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿٢٣﴾ قَالُوا۟ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّا لَن نَّدْخُلَهَآ أَبَدًا مَّا دَامُوا۟ فِيهَا فَٱذْهَبْ أَنتَ وَرَبُّكَ فَقَٰتِلَآ إِنَّا هَٰهُنَا قَٰعِدُونَ ﴿٢٤﴾ قَالَ رَبِّ إِنِّى لَآ أَمْلِكُ إِلَّا نَفْسِى وَأَخِى ۖ فَٱفْرُقْ بَيْنَنَا وَبَيْنَ ٱلْقَوْمِ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿٢٥﴾ قَالَ فَإِنَّهَا مُحَرَّمَةٌ عَلَيْهِمْ أَرْبَعِينَ سَنَةً ۛ يَتِيهُونَ فِى ٱلْأَرْضِ ۗ فَلَا تَأْسَ عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿٢٦﴾

20. Kuma (ka tuna) lokacin da Musa ya ce wa mutanensa: “Ya ku mutanena, ku tuna ni’imar Allah da Ya yi muku, yayin da Ya sanya annabawa da yawa a cikinku, kuma Ya sanya ku sarakuna, kuma Ya ba ku irin abin da bai ba wa wani cikin talikai ba.

21. “Ya ku mutanena, ku shiga ƙasar nan mai tsarki, wadda Allah Ya wajabta muku (shigarta), kuma kada ku yarda ku juya baya, sai ku komo kuna hasararru.”

22. Suka ce, “Ya kai Musa, lalle a cikinta akwai waɗansu mutane masu tsananin ƙarfi, kuma mu ba za mu shige ta ba har sai sun fita daga cikinta, don haka idan suka fita daga cikinta, to lalle za mu shiga.”

23. Waɗansu mutane biyu daga cikin masu jin tsoron (Allah), waɗanda Allah Ya yi musu ni’ima (ta imani), suka ce: “Ku shigar musu ta ƙofar (garin); idan har kun shige shi, to lalle ku masu cin nasara ne. Kuma ga Allah kaɗai za ku dogara, idan kun kasance ku muminai ne.”

24. Suka ce; “Ya kai Musa, lalle mu fa ba za mu taɓa shigar ta ba har abada, matuƙar suna cikinta; sai ka je kai da Ubangijinka ku yi yaƙin, lalle mu kam muna nan a zaune.”

25. Ya ce: “Ya Ubangijina, lalle ni ban mallaki kowa ba sai kaina da ɗan’uwana; don haka Ka yi hukunci tsakaninmu da mutanen da suke fasiƙai.”

26. Ya ce: “To lalle an haramta musu (shigarta) har tsawon shekara arba’in. Za su yi ta ɗimuwa a bayan ƙasa. Don haka kada ka yi baƙin ciki a kan mutanen da suke fasiƙai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabi (ﷺ) mugun halin Yahudawa na taurin kai da rashin bin umarnin annabawansa, don ya fahimci ba shi kaɗai ne suka yi wa taurin kai da bijire wa gaskiya bayan sun fahimce ta ba; sun yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) irin wannan bayan ni’imomi masu yawa da Allah ya yi musu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da Annabinsa (ﷺ) sa’adda Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake yi wa mutanensa Banu Isra’ila nasiha da cewa, su riƙa tuna ni’imar da

Allah ya yi musu ta aiko musu da annabawa daga cikinsu, kuma ya sanya su sarakuna, ya ba su ni'imomi masu yawa na addini da na duniya waɗanda bai taba ba wata al'umma irinsu ba.
Sannan bayan wannan tunatarwa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mutanensa sai kuma ya umarce su da lalle su shiga ƙasar Baitul Maƙadis da shirin yaƙi, su ƙwato ta daga hannun maƙiyansu, kada kuma su ja da baya a kan hakan, domin yin haka zai jefa su cikin hasararru duniya da lahira. To amma sai suka mayar masa da amsa cewa, su fa ba za su iya shiga wannan ƙasar ba, saboda a cikinta akwai wasu mutane masu ƙarfin gaske masu girman jiki waɗanda ba za su iya tunkarar su da yaƙi ba, don haka ba za su shiga wannan gari ba matuƙar waɗannan mutane suna ciki; amma idan sun fita da kansu sannan ne za su shiga.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa cikin Banu Isra'ila a lokacin akwai wasu mutane su biyu masu tsoron Allah, masu biyayya a gare shi da haƙuri da hangen nesa, sai suka nuna wa 'yan'uwansu Banu Isra'ila cewa, bai dace su noƙe su ƙi shiga Baitul Maƙadis don yaƙar waɗannan mutanen ba; abin da ya wajaba shi ne su bi umarni su shiga wannan garin ta ƙofar da ake shigarsa; idan har sun yi haka to za su yi nasara; su dogara ga Allah shi kaɗai, idan har su da gaske muminai ne. To amma abin takaici nasihar waɗannan mutanen ba ta shiga kunnuwan Banu Isra'ila ba, sai suka maimaita wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) maganarsu ta farko cewa, matuƙar dai waɗannan mutanen suna cikin garin, to fa su har abada ba za su shiga ba, sai dai shi Annabi Musa, idan har abin ya dame shi, to ya je shi da Ubangijinsa su yaƙi waɗannan ƙarfafan mutane, sannan su dawo su same su zaune suna jiran su, daga nan sai su shiga garin gaba ɗaya.
Da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ga tura ta kai bango, ya gane cewa ba zai iya tilasta wa kowa shiga wannan gari ba sai ɗan'uwansa Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kaɗai; su biyu kacal kuma ba za su iya tunkarar yaƙi ba, sai ya roƙi Allah ya yi hukunci tsakaninsa da mutanensa fasiƙai. Sai ko Allah ya karɓi addu'arsa, ya azabtar da su ta hanyar haramta musu shiga ƙasar, har tsawon shekaru arba'in suna cikin ɗimuwa da ragaita a cikin sahara, suna neman hanyar shiga wannan ƙasa amma sun kasa gano ta, sun kuma kasa zama wuri guda. Allah kuma ya hana Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna baƙin cikinsa game da wannan uƙubar da aka yi wa mutanensa, domin su ne suka jawo wa kansu, saboda sun ƙi bin umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga Annabinsa (ﷺ) da ya karantar da wannan labari na 'ya'yan Annabi Adamu su biyu, yana mai nuna muhimmancinsa a gare mu.

2. Abu ne mai kyau mu san labarin mutanen farko domin mu ɗauki darussa daga cikinsu.

3. Mutum biyu suna iya aikata wani aiki iri ɗaya na ibada, to amma sai a sami tazara a tsakaninsu wajen karɓar aikin, watau Allah ya karɓi na ɗaya daga cikinsu, ya ƙi karɓar na ɗayan.

4. Babu laifi mutum ya siffanta kansa da wani kyakkyawan hali domin yi wa ɗan'uwansa hannunka-mai-sanda a kan wannan kyakkyawan halin.

5. Hassada mummunar ɗabi'a ce wadda takan iya sa mai ita ya aikata kisan kai.

6. Wanda aka zo kashe shi bai yi yunƙurin kare kansa ba, ba shi da laifi a wurin Allah.

7. Tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana daga cikin manya-manyan dalilai da suke hana auka wa saɓon Allah da aikata miyagun laifuka.

8. Guje wa bin son zuciya mai yin umarni da aikata mummunan aiki ya kai mutum ya baro.
9. Duk mutumin da ya ƙullaci ɗan'uwansa a zuciyarsa saboda hassada, har ya yi ƙoƙarin nakasa shi, to ƙarshensa hasara ce da nadama.

10. Wannan labarin yana nuna mana cewa tun lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da ɗan'adam na farko a doron ƙasa, ya sanar da shi cewa kisa bisa zalunci haramun ne, kuma yana kai mutum shiga wutar Jahannama ranar ƙiyama.

11. Binne gawar mutum wani abu ne da ya samo asali tun farkon tarihin duniya.

12. Binne gawar ɗan'adam ita ce suturce al'aurarsa bayan mutuwarsa.

13. Ɗan'adam yakan iya koyon wani abu mai amfani daga wata dabba, kamar yadda ɗan Annabi Adamu na farko ya koyi binne gawa daga hankaka.

14. Idan lamari ya tsananta ga mutum, to Allah yakan kawo masa mafita ta inda ba ya tsammani, kamar yadda Allah ya kawo ɗan Annabi Adamu mafita ta hannun hankaka bayan ya kashe ɗan'uwansa ya daburce ya rasa yadda zai yi da gawar. Bai yi tsammanin samun mafita daga matsalarsa ba ta hanyar hankaka, sai ga shi Allah ya aiko shi.

15. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ninka uƙubar wanda ya kashe rai ɗaya ba bisa wani haƙƙi ba, da cewa kamar ya kashe mutane ne gaba ɗaya.

16. Kisan kai da yaɗa ɓarna a bayan ƙasa, manyan laifuka ne da Allah ya yi kashedi da aikata su. Tabbatar da zaman lafiya da kwanciyar hankali a cikin al'umma kuma abu ne mai matuƙar girma da muhimmanci a Musulunci; da shi ne kawai rayuwar ɗan'adam za ta tafi daidai har mutum ya samu damar ci gaba da hada-hadarsa ta yau da kullum.

17. Tsananin taurin kan al'ummar Banu Isra'ila, yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi ta aika musu manzanni, amma wannan bai amfani yawancinsu ba, bai hana su ƙetare iyakokin Ubangijinsu ba.

Suratul Ma'ida (27-32)

*وَٱتۡلُ عَلَيۡهِمۡ نَبَأَ ٱبۡنَيۡ ءَادَمَ بِٱلۡحَقِّ إِذۡ قَرَّبَا قُرۡبَانٗا فَتُقُبِّلَ مِنۡ أَحَدِهِمَا وَلَمۡ يُتَقَبَّلۡ مِنَ ٱلۡأٓخَرِۖ قَالَ لَأَقۡتُلَنَّكَۖ قَالَ إِنَّمَا يَتَقَبَّلُ ٱللَّهُ مِنَ ٱلۡمُتَّقِينَ ٢٧ لَئِنۢ بَسَطتَ إِلَيَّ يَدَكَ لِتَقۡتُلَنِي مَآ أَنَا۠ بِبَاسِطٖ يَدِيَ إِلَيۡكَ لِأَقۡتُلَكَۖ إِنِّيٓ أَخَافُ ٱللَّهَ رَبَّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢٨ إِنِّيٓ أُرِيدُ أَن تَبُوٓأَ بِإِثۡمِي وَإِثۡمِكَ فَتَكُونَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلنَّارِۚ وَذَٰلِكَ جَزَٰٓؤُاْ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٩ فَطَوَّعَتۡ لَهُۥ نَفۡسُهُۥ قَتۡلَ أَخِيهِ فَقَتَلَهُۥ فَأَصۡبَحَ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٣٠ فَبَعَثَ ٱللَّهُ غُرَابٗا يَبۡحَثُ فِي ٱلۡأَرۡضِ لِيُرِيَهُۥ كَيۡفَ يُوَٰرِي سَوۡءَةَ أَخِيهِۚ قَالَ يَٰوَيۡلَتَىٰٓ أَعَجَزۡتُ أَنۡ أَكُونَ مِثۡلَ هَٰذَا ٱلۡغُرَابِ فَأُوَٰرِيَ سَوۡءَةَ أَخِيۖ فَأَصۡبَحَ مِنَ ٱلنَّٰدِمِينَ ٣١ مِنۡ أَجۡلِ ذَٰلِكَ كَتَبۡنَا عَلَىٰ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ أَنَّهُۥ مَن قَتَلَ نَفۡسَۢا بِغَيۡرِ نَفۡسٍ أَوۡ فَسَادٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَكَأَنَّمَا قَتَلَ ٱلنَّاسَ جَمِيعٗا وَمَنۡ أَحۡيَاهَا فَكَأَنَّمَآ أَحۡيَا ٱلنَّاسَ جَمِيعٗاۚ وَلَقَدۡ جَآءَتۡهُمۡ رُسُلُنَا بِٱلۡبَيِّنَٰتِ ثُمَّ إِنَّ كَثِيرٗا مِّنۡهُم بَعۡدَ ذَٰلِكَ فِي ٱلۡأَرۡضِ لَمُسۡرِفُونَ ٣٢

27. Kuma ka karanta musu labarin gaskiya na 'ya'yan Adamu su biyu, yayin da suka gabatar da wani abin neman lada, sai aka karɓi na ɗaya daga cikinsu, ɗayan kuma ba a karɓi nasa ba, sai ya ce: "Wallahi, sai na kashe ka!" Sai ya ce: "Allah Yana karɓar aiki ne kawai daga masu taƙawa.

28. “Wallahi, idan har ka miƙa hannunka gare ni domin ka kashe ni, ni kam ba zan miƙa hannuna gare ka don in kashe ka ba; lalle ni ina jin tsoron Allah Ubangijin talikai.
29. “Lalle ni ina son ka ɗauki zunubina da zunubinka, sai ka kasance daga cikin ‘yan wuta. Kuma wannan shi ne sakamakon azzalumai.”

30. Sai zuciyarsa ta ƙawata masa ya kashe ɗan’uwansa, sai ya kashe shi, sai ya zama cikin hasararru.

31. Sai Allah Ya aiko da wani hankaka ya riƙa tona ƙasa don ya nuna masa yadda zai binne gawar ɗan’uwansa. Sai ya ce: “Kaicona! Yanzu na kasa zama kamar wannan hankakan, in je in binne gawar ɗan’uwana?” Sai ya wayi gari cikin masu nadama.

32. Saboda wannan ne muka wajabta wa Banu-Isra’ila cewa, duk wanda ya kashe wani rai ba tare da (laifin kisan) kai ba, ko kuma wata ɓarna a bayan ƙasa, to kamar ya kashe mutane ne gaba ɗaya, wanda kuwa ya raya shi, to kamar ya raya mutane ne gaba ɗaya. Kuma lalle haƙiƙa manzanninmu sun zo musu da (hujjoji) mabayyana, amma sai ga shi da yawa daga cikinsu bayan hakan, lalle masu ɓarna ne a bayan ƙasa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabinsa (ﷺ) da ya ba wa Yahudawa da sauran mutane labarin ‘ya’yan Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) su biya labari na gaskiya wanda babu ƙari a cikinsa. Lokacin da kowane ɗaya daga cikinsu ya gabatar wa da Allah abin kusanta gare shi, sai Allah ya karɓi na ɗayan bai karɓi na ɗayan ba, sai hassada ta lulluɓe shi har ya rantse sai ya kashe ɗan’uwansa. Sai shi kuma ɗan’uwan nasa ya amsa da cewa: “Allah yana karɓar aikin masu taƙawa ne kawai. Kuma idan har kai za ka ɗaga hannunka da niyyar ka kashe ni, to ni ba zan ɗaga hannuna a kanka da niyyar na kashe ka ba, saboda ni ina jin tsoron Allah. Kuma ni manufata ita ce idan ka kashe ni ka ɗauki alhakin kashe ni tare da alhakin laifukanka na baya, wannan ya sanya sanadiyyar zamantowarka ɗan wuta, kuma wannan ita ce uƙubar duk wani azzalumi.”
To amma daga ƙarshe sai zuciyarsa ta nuna masa ya kashe ɗan’uwansa, sai kuwa ya kashe shi, sai ya wayi gari a cikin waɗanda suka yi hasara duniya da lahira. Bayan ya gama mugun aikinsa na kashe ɗan’uwansa, sai kuma ya daburce, ya rasa yadda zai yi da gawar ɗan’uwansa. A daidai lokacin ne sai Allah ya aiko wani hankaka ya riƙa tona ƙasa da ƙafafuwansa yana rami, shi kuma wannan mai laifi yana kallon sa, ta haka sai ya fahimci hanyar da zai binne gawar ɗan’uwansa a ƙabari. Daga nan sai ya riƙa zargin kansa, yana cewa: “Yaya aka yi na kasa yin rami tun da farko kamar yadda wannan hankakan ya yi, ni ma in binne gawar ɗan’uwana?” Sai ya wayi gari yana mai nadamar kashe ɗan’uwansa da kuma yadda da farko ya kasa gane yadda zai yi da gawarsa.
To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, saboda wannan laifi da ɗan’adam na farko ya yi na kashe ɗan’uwansa bisa zalunci, Allah ya hukunta wa Banu Isra’ila cewa, duk wanda ya kashe wani rai ba bisa wani haƙƙi ba, na ramuwa ko na aikin ɓarna a bayan ƙasa, to kamar ya kashe mutane ne gaba ɗaya. Wanda kuma ya raya rai ɗaya, to kamar ya raya rayukan mutane ne gaba ɗaya. Sannan Allah ya bayyana cewa, manzannin Allah sun kawo wa Banu Isra’ila hujjoji bayyanannu, sai ya zamana da dama daga cikinsu sun bijire suna aikata laifuka, suna keta iyakokin Ubangiji.An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Ba wani rai da za a sake kashewa bisa zalunci, face ɗan’adam na farko (da ya yi kisa) yana da wani kamasho a cikin jinin da aka zubar, domin shi ne mutum na farko da ya sunnanta laifin kisa.” [Bukhari #3335, da Muslim #1677].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman laifin yaƙi da Allah da Manzonsa da yaɗa ɓarna a bayan ƙasa da hana zaman lafiya ta hanyar fashi da makami da aikin ta’addanci.

2. Wajibi ne a Musulunci a yanke wa masu waɗannan laifuka hukuncin da aka ambata a wannan ayar.
3. Musulunci a koyaushe yana ƙoƙarin tsarkake bayan ƙasa ne daga duk wata ɓarna, shi ya sa ya shar'anta irin wannan uƙubar mai tsanani ga masu irin waɗancan miyagun laifuka.

4. Masu aikata waɗancan miyagun laifuka da aka ambata sun cancanta a haɗa musu uƙuba biyu ne, ta duniya da ta lahira.

5. Waɗannan masu miyagun laifuka idan suka tuba kafin a kai ga kama su a hannu, to babu haddi a kansu, sai dai ga wanda ya yi kisa daga cikinsu, ko ya yi wa wani rauni, ko dukiyar wani take a hannunsa, to akwai hukuncin ramuwar kisa ko ta rauni a kansu da mayar da haƙƙoƙin waɗanda ya cuta gare su, sai dai idan suka ce sun yafe masa.

Suratul Ma'ida (33-34)

إِنَّمَا جَزَٰٓؤُاْ ٱلَّذِينَ يُحَارِبُونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَسۡعَوۡنَ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَسَادًا أَن يُقَتَّلُوٓاْ أَوۡ يُصَلَّبُوٓاْ أَوۡ تُقَطَّعَ أَيۡدِيهِمۡ وَأَرۡجُلُهُم مِّنۡ خِلَٰفٍ أَوۡ يُنفَوۡاْ مِنَ ٱلۡأَرۡضِۚ ذَٰلِكَ لَهُمۡ خِزۡيٞ فِي ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ٣٣ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُواْ مِن قَبۡلِ أَن تَقۡدِرُواْ عَلَيۡهِمۡۖ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣٤

33. Lalle sakamakon waɗanda suke yaƙar Allah da Manzonsa, kuma suke ɓarna a bayan ƙasa, shi ne kawai a karkashe su ko kuma a giggicciye su ko kuma a yayyanke hannayensu da ƙafafuwansu a tarnaƙe ko kuma a kore su daga ƙasa. Wannan ƙasƙanci ne a gare su a nan duniya, a lahira kuma suna da azaba mai girma.

34. Sai dai waɗanda suka tuba tun kafin ku sami damar ƙama su; to ku sani cewa, lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin sakamakon waɗanda suke yin fito-na-fito da Allah da Manzonsa, suna yaƙar addininsa, suna yaɗa ɓarna a bayan ƙasa, suna hana wa al'umma sakat, ta hanyar fashi da makami da ta'addanci da ƙwace wa mutane dukiyoyinsu da ƙarfi da sauran manyan laifuka. Allah ya bayyana hukuncinsu da cewa kisa ne ko a gicciye su, wato a ɗaure su a jikin wani miƙaƙken itace bayan an kashe su, ko kafin a kashe su, a shanya su kowa ya gama da ganin su. Ko a yanke musu hannayensu na dama da ƙafafuwansu na hagu, ko kuma a kore su daga ƙasar. An tanadar musu wannan hukunci ne don a kunyata su a nan duniya, a lahira kuma su gamu da azaba mai girma, ita ce wutar Jahannama.
To amma waɗanda suka tuba suka bar yaƙar addinin Allah da yaɗa ɓarna a bayan ƙasa, suka kawo kawunansu kafin a kai ga ƙama su, suka yi nadama a kan abin da suka aikata a baya, to Allah ya tabbatar wa muminai cewa shi mai gafara ne, zai gafarta musu duniya da lahira, kuma mai jin ƙai ne, zai yi musu afuwa, ba zai azabtar da su ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bawa mumini koyaushe yana neman kusanci ga Allah ne ta hanyar biyayya gare shi da kuma Manzonsa, ba ta hanyar ƙama ƙafa da wani waliyyi ko salihi ba.

2. Duk abin da bawa zai yi na ibada, to ya yi shi don Allah shi kaɗai, wannan shi ne ikhilasi.

3. Bawa yana samun kuɓuta ne a ranar gobe ƙiyama da ayyukansa na ƙwarai, ba da abin da ya mallaka ba a duniya na dukiya ko mulki ko matsayi.

4. Kafirai idan an sa su a wuta za su dawwama ne a cikinta har abada, babu ranar fita.

5. Su kuma waɗanda ba kafirai ba, wato muminai masu saɓon Allah, su za a fitar da su daga wutar Jahannama bayan an yi musu uƙubar laifukansu, a kai su Aljanna.

Suratul Ma'ida (35-37)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱبۡتَغُوٓاْ إِلَيۡهِ ٱلۡوَسِيلَةَ وَجَٰهِدُواْ فِي سَبِيلِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٣٥ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡ أَنَّ لَهُم مَّا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا وَمِثۡلَهُۥ مَعَهُۥ لِيَفۡتَدُواْ بِهِۦ مِنۡ عَذَابِ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ مَا تُقُبِّلَ مِنۡهُمۡۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٣٦ يُرِيدُونَ أَن يَخۡرُجُواْ مِنَ ٱلنَّارِ وَمَا هُم بِخَٰرِجِينَ مِنۡهَاۖ وَلَهُمۡ عَذَابٞ مُّقِيمٞ ٣٧

35. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku nemi abin da zai sada ku da shi, kuma ku yi jihadi wajen yaɗa kalmarsa, don ku rabauta.

36. Lalle waɗanda suka kafirta, in da a ce duk abin da yake ban ƙasa gaba ɗaya nasu ne, haɗe kuma da wani kamarsa, domin su fanshi kansu da shi daga azabar ranar tashin alƙiyama, da ba za a karɓa daga gare su ba; kuma suna da azaba mai raɗaɗi.

37. Suna nufin su fita daga cikin wuta, alhalin su ba masu fita ne daga cikinta ba; kuma suna da wata azaba madawwamiya.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai ne da su kiyaye dokokinsa, su nemi hanyoyin samun kusanci zuwa gare shi, kuma su yi jihadi don ɗaukaka kalmar Allah domin su sami rabauta duniya da lahira, kuma su kuɓuta daga azabar Allah, su sami abin da suke fatan samu na ni'ima ta har abada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, da a ce kafirai sun mallaki duk abin da yake cikin ƙasa, haɗe da wani kwatankwacinsa tare da shi, kuma suka so su bayar da shi domin su fanshi kansu da shi daga azabar Allah, to Allah ba zai karɓi wannan fansar ba, kuma an tanadar musu wata azaba mai raɗaɗi .An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ranar gobe ƙiyama za a kawo kafiri a ce masa: "Shin kana ganin idan abin a ce kana da zinari wanda yawansa ya cika ƙasa, za ka fanshi kanka da shi?" Sai ya ce: "E!" Sai a ce masa: "A baya can ai an buƙaci ka ba da abin da bai kai wannan ba (amma ka ƙi)." [Bukhari #6538, da Muslim #2805].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cewa, kafirai za su so su fito daga cikin wuta bayan sun ɗanɗana matsananciyar azabarta, to amma ba za a fito da su daga cikinta ba har abada; za a ci gaba da gana musu azaba mai raɗaɗi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An fara da ambaton namiji game da laifin sata, saboda ita sata tana buƙatar ƙarfin jiki da ƙarfin hali, wanda an fi samun su ga maza fiye da mata.

2. Alƙur'ani ya nuna wajibcin yanke hannun ɓarawo; ita kuma sunna ta bayyana nau'o'in satar da ake yanke hannun ɓarawo saboda ita kamar haka:
• Ya saci dukiya daga ma'ajiyarta.
• Dukiyar da ta kai nisabi, wato kimanin rubu'in dinari ko dirhami uku na azurfa, ko abin da yake daidai da su.

• Ya zama dukiya ce mai daraja.
• Ya zamanto babu wata shubuha ta mallaka a cikinta.
3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta yanke hannun ɓarawo kawai, amma sai sunna ta bayyana wurin da za a yanke watau daga tsintsiyar hannunsa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta wa al'umma zartar da hukuncin yanke hannun ɓarawo. Wannan ya nuna dole ne a sami shugaba a cikin kowace al'umma da zai ɗauki nauyin zartar da waɗannan hukunce-hukunce, idan kuma ya ƙi aiki da su, dole ne a kan al'umma ta ci gaba da neman a dawo da aiki da shari'ar Allah a cikinsu.

5. An yi umarni da yanke hannun wanda ya yi sata a matsayin haddi, domin da hannun ake amfani wajen yin satar. Kuma ana yanke hannun dama, saboda galibi da shi aka fi amfani wajen satar.

6. Hikimar zartar da haddin sata a kan ɓarawo, don ya zama wa'azi gare shi da mai tunani irin nasa.

7. Ɓarawo idan ya tuba kafin a kama shi, to babu haddin sata a kansa, amma zai mayar wa da mutane kayansu da ya ɗauka, sai dai in sun yafe masa.

Suratul Ma'ida (38-40)

وَٱلسَّارِقُ وَٱلسَّارِقَةُ فَٱقْطَعُوٓاْ أَيْدِيَهُمَا جَزَآءًۢ بِمَا كَسَبَا نَكَٰلًا مِّنَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٣٨﴾ فَمَن تَابَ مِنۢ بَعْدِ ظُلْمِهِۦ وَأَصْلَحَ فَإِنَّ ٱللَّهَ يَتُوبُ عَلَيْهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٣٩﴾ أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ يُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ وَيَغْفِرُ لِمَن يَشَآءُ ۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٤٠﴾

38. Kuma ɓarawo da ɓarauniya, sai ku yanke hannayensu, wannan sakamako ne na abin da suka aikata, uƙuba ce daga Allah. Kuma Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.

39. To (amma) wanda ya tuba bayan zaluncinsa, kuma ya gyara aikinsa, to lalle Allah zai karɓi tubansa. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

40. Shin ba ka da masaniyar cewa, lalle Allah Shi ne Yake mallakar abin da yake cikin sammai da kuma ƙasa, Yana yin azaba ga wanda Ya ga dama, kuma Yana gafarta wa wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mai iko ne a kan komai?

A nan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zo da hukuncin ɓarawo, namiji ne ko mace, wato a yanke hannunsa na dama daga kan tsintsiyar hannu, sakamakon satar dukiyar da ba tasa ba, don wannan ya zama gargadi a gare shi, kuma ya zama darasi ga wani mai son aikata irin laifinsa. Kuma Allah Gagara badau ne, babu abin da ya fi ƙarfinsa, kuma Gwani ne mai hikima cikin duk hukunce-hukuncensa. To amma wanda ya tuba ya bar sata, ya daina zaluntar kansa da waninsa, ya koma ga Allah ya gyara halinsa, to wannan Allah zai karɓi tubansa. Lalle Allah mai gafara ne, mai jin ƙai.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci buwayarsa da girman mulkinsa da zartuwar hukuncinsa, da cewa, shi ne fa mamallakin sammai da ƙasa, yana azabtar da wanda ya ga dama da adalcinsa, kuma ya yi gafara ga wanda ya ga dama da falalarsa; duk bayi kuma mulkinsa ne, kuma a hannunsa al'amuransu suke, kuma shi mai iko ne a kan komai; babu abin da zai gagare shi ko ya fi ƙarfinsa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kiran da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi wa Manzonsa da: “Ya kai wannan Manzon...” ko “Ya kai wannan Annabi...,” wata koyarwa ce da tarbiyya ga muminai da kada su riƙa kiransa da tsurar sunansa.
2. Imani da gyaruwa da lalacewa duk daga zuciya suke samo asali; sai idan imani ya zauna a zuciya sannan ne yake zamantowa karbaɓbe.

3. Mutane sun sha bamban wajen kafircinsu; kafircin wani ya fi na wani. Wani yana gudu ne a cikin kafirci; wani sauri yake; wani kuma tafiya yake. Wanda yake kafirin kuma yana kiran mutane zuwa ga kafirci shi ne mai gudu ko mai gaggawa a kafircinsa; wanda kuma ba ya kira shi ne marar gaggawa.

4. Duk malamin da yake canza ma’anonin ayoyin Allah na haƙiƙa da wasu ma’anoni daban na son zuciya, to wannan malami yana kama da Yahudawa.

5. Wanda ya canza ma’anonin ayoyin Allah yana sane, shi ne abin suka, ba wanda ya canza bisa rashin sani ba.

6. Waɗanda ba sa karɓar gaskiya sai idan ta yi daidai da son ransu su ne abin suka.

7. Ya kamata ga mutum a kodayaushe ya yi ta ƙoƙarin aikata abin da zai tsarkake zuciyarsa. Tsarkin zuciya yana gaba da tsarkin jiki. Munafiƙi ba shi da tsarkin zuciya, amma zai iya zama mai tsarkin jiki.

8. Guje wa sauraron ƙarairayi da yaɗa su da aiki da su, domin wannan hali ne na Yahudawa.

9. Guje wa cin dukiyar mutane ba bisa gaskiya ba, domin shi ma wannan hali ne na Yahudawa.

10. Ba ya halatta ga mai yin wani hukunci ya nuna son kai ga wani ɗan’uwansa ko abokinsa ko masoyinsa. Lalle ya yi hukuncinsa don Allah da adalci.

11. Allah yana kwaɗaitar da bayinsa su zama masu adalci, domin yana son adalci a komai. An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya kara masa yarda) daga Annabi (ﷺ) yana cewa: “Masu adalci suna kan wasu minbarori na haske a wajen Allah, a dama da Allah mai rahama, dukkan hannayensa biyu dama ne, su ne masu yin adalci a cikin hukuncinsu da iyalansu da abin da aka shugabantar da su a kai.” [Muslim #1824].

12. Wanda yake neman fatawa wajen wani malami don kawai ya samu sauƙi, to wannan ya yi kama da Yahudawa.

13. Yana daga cikin miyagun halayen Yahudawa, kasancewar ba sa karɓar gaskiya sai wadda ta yi daidai da son ransu.

Suratul Ma’ida (41-43)

۞يَٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ لَا يَحۡزُنكَ ٱلَّذِينَ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡكُفۡرِ مِنَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِأَفۡوَٰهِهِمۡ وَلَمۡ تُؤۡمِن قُلُوبُهُمۡۛ وَمِنَ ٱلَّذِينَ هَادُواْۛ سَمَّٰعُونَ لِلۡكَذِبِ سَمَّٰعُونَ لِقَوۡمٍ ءَاخَرِينَ لَمۡ يَأۡتُوكَۖ يُحَرِّفُونَ ٱلۡكَلِمَ مِنۢ بَعۡدِ مَوَاضِعِهِۦۖ يَقُولُونَ إِنۡ أُوتِيتُمۡ هَٰذَا فَخُذُوهُ وَإِن لَّمۡ تُؤۡتَوۡهُ فَٱحۡذَرُواْۚ وَمَن يُرِدِ ٱللَّهُ فِتۡنَتَهُۥ فَلَن تَمۡلِكَ لَهُۥ مِنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗاۚ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَمۡ يُرِدِ ٱللَّهُ أَن يُطَهِّرَ قُلُوبَهُمۡۚ لَهُمۡ فِي ٱلدُّنۡيَا خِزۡيٞۖ وَلَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ٤١ سَمَّٰعُونَ لِلۡكَذِبِ أَكَّٰلُونَ لِلسُّحۡتِۚ فَإِن جَآءُوكَ فَٱحۡكُم بَيۡنَهُمۡ أَوۡ أَعۡرِضۡ عَنۡهُمۡۖ وَإِن تُعۡرِضۡ عَنۡهُمۡ فَلَن يَضُرُّوكَ شَيۡـٔٗاۖ وَإِنۡ

حَكَمۡتَ فَٱحۡكُم بَيۡنَهُم بِٱلۡقِسۡطِۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُقۡسِطِينَ ٤٢ وَكَيۡفَ يُحَكِّمُونَكَ وَعِندَهُمُ ٱلتَّوۡرَىٰةُ فِيهَا حُكۡمُ ٱللَّهِ ثُمَّ يَتَوَلَّوۡنَ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَۚ وَمَآ أُوْلَٰٓئِكَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٤٣

41. Ya kai wannan Manzo, kar waɗannan da suke gaggawa cikin kafirci su baƙanta maka rai, daga cikin waɗanda suka ce: “Mun yi imani” da bakunansu, amma zukatansu ba su yi imani ba; da kuma waɗanda suke Yahudawa, masu yawan sauraron ƙarya, masu yawan sauraron waɗansu mutanen da ba su zo wajenka ba; suna caccanja kalmomi daga wurarensu, suna cewa: “Idan an ba ku wannan, to ku karɓe shi, idan kuwa ba shi aka ba ku ba, to ku yi hattara.” Duk kuwa wanda Allah Ya nufi fitinar sa, to ba abin da za ka iya mallaka masa daga wurin Allah. Waɗannan su ne waɗanda Allah bai yi nufin Ya tsarkake zukatansu ba. A nan duniya suna da ƙasƙanci, a lahira kuma suna da azaba mai girma.

42. (Su ne) masu yawan sauraron ƙarya, masu yawan cin haram. Don haka idan sun zo maka, to ka yi musu hukunci, ko ka kau da kai daga gare su; idan kuwa ka kawar da kai daga gare su, to ba za su cutar da kai da komai ba; idan kuwa za ka yi hukuncin, to ka yi hukunci tsakaninsu da adalci. Lalle Allah Yana son masu adalci.

43. Kuma ta yaya za su kawo maka hukunci, alhalin Attaura tana wurinsu, a cikinta akwai hukuncin Allah, sannan su juya baya bayan haka? Waɗannan kam ba muminai ba ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rarrashin Annabinsa (ﷺ) ne da cewa, kada Yahudawa masu gaggawar shiga cikin kafirci su baƙanta masa rai, da kuma munafuƙai masu bayyana imaninsu a fatar baki kawai, amma bai shiga zukatansu ba, da Yahudawan da suke ƙasa kunnuwa su saurari ƙarairayin da malamansu da shugabanninsu suke faɗa musu ko da yaushe, suna kuma bin umarnin wasu malamansu da shugabanninsu waɗanda suka bijire wa Annabi (ﷺ) ba sa halartar majalisarsa. To waɗannan su ne masu canza maganar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) su kawo wata wadda ta yi daidai da son ransu da gangan, alhalin sun san gaskiya. Suna faɗa wa mabiyansu cewa: “Ku je ku kai ƙara wajen Muhammadu, idan ya yi muku hukuncin da ya yi daidai da son ranku, to ku yarda, idan kuwa ya yi muku hukuncin da ya saɓa da son ranku, to kada ku yarda.”
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gaya wa Annabinsa cewa, wanda duk ya nufi ya fitine shi, to bai mallaki wani abu daga Allah ba, wanda zai kuɓutar da shi daga ɓata. Amma su Yahudawan da ba sa karɓar wata gaskiya sai wadda ta dace da son zukatansu, to waɗannan Allah bai nufi tsarkake zukatansu daga ƙazantar shirka da kafirci ba, kuma suna tare da wulaƙanci da ƙasƙanci a nan duniya, a lahira kuwa za su gamu da azaba mai tsanani ta wutar Jahannama. Waɗannan Yahudawa da ma sun saba da sauraron ƙarairayi da yawan cin dukiyar haram, kamar ta rashawa da riba da sauransu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabinsa (ﷺ) zaɓin cewa, idan waɗannan mutane sun kawo masa hukunci, to yana kuma da damar ya yi musu hukunci, yana da damar ya rabu da su ya ƙyale su, domin ko da ya ƙyale su, wannan ba zai cutar da shi da komai ba. Idan kuma ya zaɓi zai yi musu hukunci, to ya yi musu hukunci na adalci. Allah yana son mutane masu adalci.

An karɓo daga Al-Bara’u ɗan Azib (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “An wuce ta gaban Annabi (ﷺ) da wani Bayahude, wanda aka shafe fuskarsa da baƙin gawayi, aka yi masa bulala, sai Annabi (ﷺ) ya kirawo su ya ce musu: “Haka kuka sami bayanin haddin mazinaci a littafinku?” Sai suka ce: “E!” Sai Annabi (ﷺ) ya kirawo ɗaya daga cikin malamansu, ya ce masa: “Na haɗa ka da Allah, haka kuka sami bayanin haddin mazinaci a cikin littafinku?” Sai ya ce: “A’a. Ba don ka haɗa ni da Allah ba, da ba zan faɗa maka ba. Hukuncin da yake cikin littafinmu shi ne jefewa, sai dai da yake zinace-zinace sun yi yawa a cikin manyan mutanenmu, sai ya zamana duk sa’adda muka kama babban mutum da laifin zina, sai mu ƙyale shi ba tare da mun hukunta shi ba, to amma idan muka kama talaka, sai mu tsayar masa da haddi. Sai kuma

daga baya muka haɗu muka zartar da hukunci guda ɗaya, wanda zai shafi babban mutum da talaka. Sai muka musanya hukuncin jefewa da shafe fuska da baƙin gawayi da bulala."
Sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Ya Allah, ni ne farkon wanda ya raya wannan hukunci naka bayan sun kashe shi." Sai ya ba da umarni aka jefe wannan Bayahude. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "Ya kai wannan Manzo, kada waɗanda suke gaggawa cikin kafirci su baƙanta maka rai...." har zuwa faɗarsa: "….in an ba ku wannan, to ku karɓa." Yana cewa: "Ku je ga Muhammadu (ﷺ), idan ya umarce ku da ku sanya ma mazinaci baƙin gawayi a fuska, ku yi masa bulala, to ku yarda da wannan hukunci, idan kuwa ya ba ku fatawa ne da jefewa, to ku guje shi." Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "Wanda bai yi hukunci da abin da Allah ya saukar ba, to waɗannan su ne kafirai…" [Muslim #1700].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, ta yaya waɗannan Yahudawa za su sanya ka mai hukunci a tsakaninsu, alhalin suna ƙaryata ka, sannan ga littafin Attaura nan a hannunsu, amma kuma sun bijire masa, sun yi watsi da shi, sun tafi neman wani hukunci daban wanda suke son ya yi daidai da son zukatansu? Mutanen da wannan shi ne aikinsu ai ba muminai ne ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin matsayin Attaura, wadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), wadda take ɗauke da shiriya da haske.

2. Mutum ya jingina kansa ga wani addini na annabawa kawai ba shi ne zai amfane shi ba; aiki da karantarwar wannan addini da biyayya ga annabin da Allah ya aiko, shi ne abin la'akari a wajen Allah.

3. Littafin Attaura shi ne littafin da annabawan Banu Isra'ila suka riƙa hukunci da shi bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

4. Malamai su ne magadan annabawa wajen bayanin shari'a da kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Bayani a kan cewa abubuwa biyu ne suke sanya mutum ya kauce wa addinin Allah ya ɓoye gaskiya, watau: tsoron mutane da kwaɗayin abin duniya, na dukiya ko shugabanci da makamantansu.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗora wa malaman Banu Isra'ila alhakin tsare littafin Attaura, amma sai wasu suka yi watsi da wannan nauyin suka dina jirkita wasu ma'anoninsa. Amma shi Alƙur'ani Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne da kansa ya ɗauki gabaren tsare kayansa da kansa, don haka babu wanda ya isa ya canza wani abu daga cikinsa.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta yin ramuwa ne a kan kashe wani rai ko yi masa rauni ko cire masa wata gaɓa tasa, ba tare da la'akari da cewa shi babban mutum ne ko ƙarami, mai wadata ne ko matalauci, ko yaro ne ko babba, mai ilimi ne ko jahili.

8. Kwaɗaitarwa a kan yin afuwa ga mai laifi.

9. Girman haɗarin watsi da shari'ar Allah da yin hukunci da abin da ya saɓa wa hukuncin Allah.

10. Aiki da hukuncin da ya saɓa wa hukuncin Allah mataki-mataki ne, kamar haka:

i. Wanda duk ya zaɓi hukuncin da ba na Allah ba don yana ganin ya fi hukunci Allah amfani, ko yana ganin hukuncin Allah babu adalci a cikinsa, ko domin ya tsani hukuncin Allah, ko kuma yana ganin da hukuncin Allah da wanda ba na Allah ba duk ɗaya ne babu bambanci, ko kuma hukuncin Allah bai dace da zamani ba, to duk waɗannan kafirci ne mai fitar da mutum daga Musulunci. Ana yi wa mai wannan ra'ayi hukuncin kafirci idan sharuɗɗan kafirta shi sun cika, kuma duk wani uzuri ya kau daga kansa.
ii. Wanda zai canza hukuncin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a kan wani hukunci na musamman don son zuciya ko zalunci, ba tare da ya mayar da shi doka ba ta bai-ɗaya, to wannan saɓon Allah ne, zalunci ne, ba zai fitar da shi da ga Musulunci ba.
iii. Wanda ya saɓa wa hukuncin Allah don bin son zuciya ko wata masalaha ta kansa, to wannan fasiƙi ne, ba kafiri ba. [Dubi, *Majmu'u Fatawa Ibnul* Uthaimeen 2:145].
Kafirta mai hukunci da wani abu ba shari'ar Allah ba yana da sharuɗɗa kamar haka:
Na ɗaya: Mai hukunci ya zamanto ya san hukuncin Allah, amma ya saba masa.
Na biyu: Ya san cewa wannan hukuncin ya saba wa na Allah, amma ya zaɓe shi.
Na uku: Ya fifita shi ko ya daidaita shi da na Allah, ya zaɓe shi madadin hukuncin Allah.
Na huɗu: Ya yarda da cewa wannan hukuncin shi ne na daidai. [Dubi Tafsirin Ibn Uthaimeen, *Suratul Ma'ida*, Juzu'i na 1, Shafi na 435-436].

Suratul Ma'ida (44-45)

إِنَّآ أَنزَلۡنَا ٱلتَّوۡرَىٰةَ فِيهَا هُدٗى وَنُورٞۚ يَحۡكُمُ بِهَا ٱلنَّبِيُّونَ ٱلَّذِينَ أَسۡلَمُواْ لِلَّذِينَ هَادُواْ وَٱلرَّبَّٰنِيُّونَ وَٱلۡأَحۡبَارُ بِمَا ٱسۡتُحۡفِظُواْ مِن كِتَٰبِ ٱللَّهِ وَكَانُواْ عَلَيۡهِ شُهَدَآءَۚ فَلَا تَخۡشَوُاْ ٱلنَّاسَ وَٱخۡشَوۡنِ وَلَا تَشۡتَرُواْ بِـَٔايَٰتِي ثَمَنٗا قَلِيلٗاۚ وَمَن لَّمۡ يَحۡكُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ٤٤ وَكَتَبۡنَا عَلَيۡهِمۡ فِيهَآ أَنَّ ٱلنَّفۡسَ بِٱلنَّفۡسِ وَٱلۡعَيۡنَ بِٱلۡعَيۡنِ وَٱلۡأَنفَ بِٱلۡأَنفِ وَٱلۡأُذُنَ بِٱلۡأُذُنِ وَٱلسِّنَّ بِٱلسِّنِّ وَٱلۡجُرُوحَ قِصَاصٞۚ فَمَن تَصَدَّقَ بِهِۦ فَهُوَ كَفَّارَةٞ لَّهُۥۚ وَمَن لَّمۡ يَحۡكُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٤٥

44. Lalle Mu Muka saukar da Attaura, (wadda) a cikinta akwai shiriya da haske. Annabawa waɗanda suka miƙa wuya suna hukunci da ita, ga waɗanda suke Yahudawa, da malamai na-Allah da malamai masana, saboda abin da aka ɗora musu na kiyaye Littafin Allah, kuma sun kasance masu ba da shaida a kansa. Don haka kada ku ji tsoron mutane, ku ji tsoro Na Ni kaɗai, kuma kada ku musanya ayoyina da wani ɗan farashi ƙanƙani. Duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba kuwa, to waɗannan su ne kafirai.

45. Kuma Mun wajabta a kansu a cikinta (Attaura), lalle rai da rai, kuma ido da ido, kuma hanci da hanci, kuma kunne da kunne, kuma haƙori da haƙori, raunuka kuma a yi ramuwa. To duk wanda ya yi sadaka da shi, to wannan kaffara ce gare shi. Duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba kuwa, to waɗannan su ne azzalumai.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa ya saukar wa Annabi Musa littafin Attaura, wanda yake ƙunshe da shiriya da haskensa, annabawa kuma waɗanda suka miƙa wuya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) suna yin hukunci da shi a tsakanin Yahudawa. Hakanan malamai na Allah da manyan malaman Yahudawa su ma suna yin hukunci da shi saboda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su amanar kula da shi, ya umarce su da su kiyaye shi, su bayyana shi kuma su kare shi daga duk wani ƙari ko ragi, kuma masu shaidar cewa littafi ne da Allah ya saukar, wanda yake ƙunshe da hukuncin Allah, Allah kuma ya umarce su da kada su ji tsoron mutane wajen zartar da hukuncin Allah; su ji tsoron sa shi kaɗai. Ya kuma yi musu kashedi da musanya hukuncinsa da wani ɗan jin daɗi kaɗan na duniya. Sannan ya tabbatar musu da cewa duk wanda ya yi hukunci ba da abin da Allah ya saukar ba, to waɗannan su ne kafirai.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin cewa ya wajabta wa Yahudawa hukuncin ramuwa a cikin littafin Attaura, wato a kashe duk wanda ya kashe wani da gangan ba tare da haƙƙi ba, haka kuma wanda ya cire idon wani shi ma a cire masa, ko hanci a cire nasa, ko kunne a cire nasa, ko haƙori a cire nasa, kamar yadda ya wajabta yin ramuwa a rauni. Duk wanda ya yi wa wani rauni bisa zalunci, to ya nemi ramuwa kwatankwacin raunin da aka yi masa. Amma duk wanda ya yi afuwa, ya yafe wa wanda ya yi masa laifi, to Allah zai kankare masa laifukansa, sakamakon afuwar da ya yi. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya daɗa tabbatar da cewa duk wanda bai yi hukunci da abin da ya saukar ba, to waɗannan su ne azzalumai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne ƙarshen annabawan Banu Isra'ila, babu wani annabi da ya biyo bayansa sai Annabi Muhammad (ﷺ).

2. Wanda ba shi da uba ana iya kiran sa da sunan mahaifiyarsa, kamar yadda aka jingina Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ga mahaifiyarsa, aka ce Isa ɗan Maryam, domin ba shi da uba.

3. Kwaɗaitarwa a kan tsoron Allah da cewa shi ne tushen duk wani alheri, kuma dalilin samun ilimi, kuma ginshiƙin gina aiki na ƙwarai.

Suratul Ma'ida (46-47)

وَقَفَّيْنَا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم بِعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ ۖ وَءَاتَيْنَٰهُ ٱلْإِنجِيلَ فِيهِ هُدًى وَنُورٌ وَمُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَهُدًى وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ﴿٤٦﴾ وَلْيَحْكُمْ أَهْلُ ٱلْإِنجِيلِ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فِيهِ ۚ وَمَن لَّمْ يَحْكُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿٤٧﴾

46. Sai Muka biyar da Isa ɗan Maryamu a bayansu wanda yake gaskata abin da ya gabace shi na Attaura, kuma Muka ba shi Linjila, a cikinta akwai shiriya da haske, kuma tana gaskata abin da ya gabace ta na Attaura, kuma shiriya ce, da wa'azi ga masu taƙawa.

47. Lalle kuma ma'abota Linjila su yi hukunci da abin da Allah Ya saukar a cikinsa. Duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah Ya saukar ba kuwa, to waɗannan su ne fasiƙai.

A waɗannan ayoyi kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, ya aiko da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan annabawan Banu Isra'ila masu hukunci da Attaura. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuma ya yi imani da littafin Attaura, yana ba da shaidar cewa Attaura gaskiya ce. Shi kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi littafin Linjila, wanda shi ma cike yake da shiriya da haske, yana mai shaida da tabbatar da abin da yake cikin littafin Attaura, yana bayanin gaskiya, yana gargaɗin masu tsoron Allah da su ƙaurace wa haramun da aikata laifuka.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Nasara da su yi hukunci da abin da yake cikin littafin Linjila wanda ya saukar wa Annabi Isa(Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su yi aiki da shi, su yi imani da duk abin da ya ƙunsa, wanda ya haɗa har da albishir da Allah ya yi na aiko Annabi Muhammad (ﷺ) da umarni kan su yi imani da shi, kuma su yi masa biyyaya. Sannan Allah ya tabbatar da cewa duk wanda bai yi hukunci da abin da Allah ya saukar ba, to waɗannan su ne fasiƙai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne Musulmi su zama masu tsayuwa ne da ƙafafuwansu, masu ji da girmansu na Musulmi; kada su zama ‘yan amshin Shata ga maƙiyansu kafirai, su dinga yi musu biyayya sau-da-ƙafa; yin haka ƙaƙƙanci ne da tozarta kai.

2. Allah ya gargaɗi Annabi (ﷺ) da cewa kada ya bi son zuciyar Yahudawa, duk da cewa, abu ne sananne Annabi ba zai yi hakan ba. Wannan yana nuna mana girman haɗarin biyayya ga manufofin Yahudawa da Nasara a rayuwarmu.

3. Bayanin cewa, dole a sami saɓani a rayuwar mutane, ba za su zama abu ɗaya ba.

4. Bayanin haɗarin aukawa cikin zunubai; duk lokacin da zunubin bawa yake ƙaruwa, to yana ƙara nisanta shi ne daga bin shari’ar Allah.

5. Hukuncin Allah ya fi kowane hukunci inganci da adalci. Don haka yayin da bawa ya fahimci haka, to zai ƙara miƙa wuya ga hukunnce-hukuncen Ubangijinsa ko da kuwa bai gane hikimar da take cikinsu ba.

6. Shari’ar Alƙur’ani ta goge duk wata shari’a ta annabawan da suka gabata.

7. Idan Yahudawa ko Nasara suka zaɓi mu yi musu hukunci, to dole ne mu yi aiki da shari’ar Musulunci, ba da abin da suke so ba.

8. Duk abin da Yahudawa da Nasara suke a kai wanda ya saɓa wa shari’ar Allah, to son zuciya ne, babu gaskiya a cikinsa.

9. Nuni a kan ƙiyayyar Yahudawa da Nasara ga Musulmi da bayanin cewa babbar manufarsu ita ce su samu kautar da Musulmi daga Musulunci, su raba su da Alƙur’ani.

10. Duk wani hukunci da ya saɓa wa na Allah, to hukunci ne na jahiliyya.

Suratul Ma’ida (48-50)

وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَمُهَيۡمِنًا عَلَيۡهِۖ فَٱحۡكُم بَيۡنَهُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُۖ وَلَا تَتَّبِعۡ أَهۡوَآءَهُمۡ عَمَّا جَآءَكَ مِنَ ٱلۡحَقِّۚ لِكُلّٖ جَعَلۡنَا مِنكُمۡ شِرۡعَةٗ وَمِنۡهَاجٗاۚ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَكُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَلَٰكِن لِّيَبۡلُوَكُمۡ فِي مَآ ءَاتَىٰكُمۡۖ فَٱسۡتَبِقُواْ ٱلۡخَيۡرَٰتِۚ إِلَى ٱللَّهِ مَرۡجِعُكُمۡ جَمِيعٗا فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ ٤٨ وَأَنِ ٱحۡكُم بَيۡنَهُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ وَلَا تَتَّبِعۡ أَهۡوَآءَهُمۡ وَٱحۡذَرۡهُمۡ أَن يَفۡتِنُوكَ عَنۢ بَعۡضِ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ إِلَيۡكَۖ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَٱعۡلَمۡ أَنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُصِيبَهُم بِبَعۡضِ ذُنُوبِهِمۡۗ وَإِنَّ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلنَّاسِ لَفَٰسِقُونَ ٤٩ أَفَحُكۡمَ ٱلۡجَٰهِلِيَّةِ يَبۡغُونَۚ وَمَنۡ أَحۡسَنُ مِنَ ٱللَّهِ حُكۡمٗا لِّقَوۡمٖ يُوقِنُونَ ٥٠

48. Kuma Mun saukar maka da Littafin (Alƙur’ani) da gaskiya, yana mai gaskata abin da ya gabace shi na sauran littattafai, kuma mai ɗaukaka a kansu; don haka ka yi hukunci a tsakaninsu da abin da Allah Ya saukar; kuma kada ka bi soye-soyen zukatansu ka bar abin da ya zo maka na gaskiya don bin son zuciyarsu. Kowanne daga cikinku Mun sanya musu tsari na shari’a da tsari na rayuwa. Kuma in da Allah Ya ga dama, da sai Ya sanya ku ku zamo al’umma ɗaya, sai dai kuma don Ya jarrabe ku cikin abin da Ya ba ku; don haka sai ku yi gaggawar aikata ayyuka na alheri. Gaba ɗaya makomarku zuwa ga Allah take, kuma zai ba ku labarin abin da kuka kasance kuna saɓani a kansa.

49. Kuma ka yi hukunci a tsakaninsu da abin da Allah Ya saukar, kuma kada ka bi soye-soyen zukatansu, kuma ka yi hattara da su, don kada su fitine ka ka bar wani sashi na abin da Allah Ya saukar maka; idan kuwa sun juya baya, to ka sani lalle Allah Yana nufin Ya kama su ne da wani sashi na zunubansu. Kuma lalle yawancin mutane fasiƙai ne.

50. Shin hukuncin jahiliyya suke nema ne? To wane ne ya fi Allah kyakkyawan hukunci ga mutanen da suke da sakankancewa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana jaddada cewa, shi ya aiko wa Annanbi (ﷺ) Alƙur'ani da gaskiya, yana shaida yana kuma gaskata littattafan da Allah ya saukar gabaninsa wanda yake ƙunshe da abin da suka zo da shi yana kuma hukunci a kansu. To sai Allah ya umarci Ma'aiki da ya yi hukunci tsakanin Ma'abota Littafi da shi wannan Alƙur'anin a duk sanda suka kawo masa hukunci. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya hana shi bin son zuciyarsu wanda ya ci karo da gaskiyar da ta zo masa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa, kowace alumma ya sanya mata tsarin shari'a da kuma tsarin rayuwa. Da ya ga dama da sai ya sanya mutane gaba ɗayansu a kan shari'a da tsarin rayuwa iri ɗaya; to amma saboda Allah ya jarrabi bayinsa, sai ya sanya wa kowace al'umma tsarin shari'arta da tsarin rayuwarta daban. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni ga bayinsa su riƙa yin rigegeniya wajen aikata alheri, domin makomar bayi gaba ɗayansu zuwa gare shi ne, kuma zai labarta wa mutane abin da suka kasance suna saɓani a kansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa (ﷺ) da ya yi musu hukunci da Alƙur'anin da ya saukar masa, kada ya bi son zuciyarsu, kuma ya yi hattara da su kada su kautar da shi, ya bar aiki da abin da Allah ya saukar masa. Idan sun bijire wa hukuncinsa, to ya sani cewa Allah ne zai yi musu uƙuba saboda laifukansu. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa mutane da dama ba sa yi wa Ubangijinsu biyayya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci waɗannan Yahudawa da cewa, shin suna so ne a riƙa yi musu hukuncin da ya saɓa wa gaskiya, wanda aka gina shi a kan zalunci da jahilci? Sai ya bayyana ƙarara cewa babu wani hukuncin da ya yi kyan hukuncin Allah ga duk wanda ya yi imani da Allah, ya zamanto mai sakankancewa da shi zai fahimci hakan cikin sauƙi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kiran muminai da siffarsu ta imani, yana nuna girman sha'aninsu ne wajen guje wa taimakon kafirai a kan cutar da Musulmi, wato yin hakan yana daga cikin hukunce-hukuncen imani. Mayar da su kuma abokai yana nuna tawaya a cikin imanin bawa, ko ma ya kawar da shi gaba ɗaya daga sahun muminai idan ya kai matakin yaƙar Musuluncin da shari'arsa.

2. Yahudawa da Nasara da sauran kafirai sukan iya haɗa kai wajen yaƙar Musulunci da Musulmi. Don haka wajibi ne su ma Musulmi su zama tsintsiya maɗaurinki ɗaya, su yi watsi da duk wasu bambance-bambance na siyasa ko ra'ayi, domin tinkarar maƙiyansu da kare kawunansu da addininsu.

3. Duk wanda yake cikin Musulmi kuma ya ɗauki salon taimakon Yahudawa da Nasara wajen faɗa da Musulmi, to ya sani cewa ya zalunci kansa, kuma idan bai tuba ya bari ba, to Allah ba zai nuna masa hanyar shiriya ba.

4. Duk wanda yake gaggawar taimakon kafirai don cutar da Musulmai, to akwai cutar shakka da kokwanto a zuciyarsa, kuma wannan cutar mai hauhawa ce, har ta kai shi ga kafirci.

5. Munafuƙai a cikin wannan al'umma su ne masu haɗa kai da kafirai domin cutar da ita.

6. Albishir ga muminai na cewa su ne masu samun galaba da cin nasara a kan maƙiyansu kafirai komai daɗewar lokaci, kuma Allah ya wajabta wa kansa zai ba su nasara.

7. Duk wani munafuki komai daɗewa dole ne sai asirinsa ya tonu, kuma ya kunyata.

8. Munafuƙai manyan maƙaryata ne, har kullum suna nuna wa muminai cewa suna tare da su wajen imani da taimakon addini, bisa yaudara don su sami damar yaɗa ɓarnarsu a cikin al'umma.
9. Munafuƙai sukan yi rantsuwa da sunan Allah, suna nuna su masu ganin girman Allah ne, har ma suna salla, suna ambaton Allah, amma duka wannan ba zai yi musu amfani ba a ranar alƙiyama.

10. Duk yadda al'amari ya kaya, munafuki ba zai taɓa cin riba ba, sai dai ya yi hasara. Idan Allah ya tona masa asiri a duniya, to ya yi asara, mutane za su ƙyamace shi, idan kuma Allah ya rufa masa asiri a nan duniya, to zai kunyata a lahira, don haka ya yi asarar duniya da lahira gaba ɗaya.

Suratul Ma'ida (51-53)

*يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ ٱلۡيَهُودَ وَٱلنَّصَٰرَىٰٓ أَوۡلِيَآءَۘ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمۡ فَإِنَّهُۥ مِنۡهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥١ فَتَرَى ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ يُسَٰرِعُونَ فِيهِمۡ يَقُولُونَ نَخۡشَىٰٓ أَن تُصِيبَنَا دَآئِرَةٞۚ فَعَسَى ٱللَّهُ أَن يَأۡتِيَ بِٱلۡفَتۡحِ أَوۡ أَمۡرٖ مِّنۡ عِندِهِۦ فَيُصۡبِحُواْ عَلَىٰ مَآ أَسَرُّواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ نَٰدِمِينَ ٥٢ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَهَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ أَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ إِنَّهُمۡ لَمَعَكُمۡۚ حَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡ فَأَصۡبَحُواْ خَٰسِرِينَ ٥٣

51. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi Yahudawa da Nasara masoya. Sashinsu masoya sashi ne. Duk kuwa cikinku wanda ya jiɓinci lamarinsu, to lalle shi yana cikinsu. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai.

52. Sai ka ga waɗanda suke da cuta a cikin zukatansu suna gaggawa a ciki (jiɓintar su), suna cewa: "Muna jin tsoron kar wata musiba ta same mu." To mai yiwuwa ne Allah Ya zo da buɗi ko wani lamari daga gare Shi, sai su wayi gari suna nadama kan abin da suka riƙa ɓoyewa a zukatansu.

53. Kuma waɗanda suka yi imani suna cewa: " Yanzu waɗannan su ne waɗanda suka rantse da Allah iya ƙurewar rantsuwarsu; cewa, lalle suna tare da ku?" Ayyukansu sun rushe, don haka sai suka wayi gari suna masu hasara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana hana muminai taimakon Yahudawa da Nasara da nuna musu ƙauna. Ya sanar da cewa Yahudawa suna taimaka wa Yahudawa 'yan'uwansu, hakanan Nasara suna taimaka wa junansu wajen faɗa da Musulmai, don haka duk wani Musulmi da ya taimaka wa Yahudawa ko Nasara wajen faɗa da 'yan'uwansa Musulmi, to ya zama ɗaya daga cikinsu. Allah ba ya shiryar da mutanen da suka zama azzalumai, masu irin wannan sabgar.
Sannan Allah Ta'ala ya yi wa Annabinsa (ﷺ) hannunka-mai-sanda cewa, zai ga munafuƙai waɗanda zukatansu suka cika da shakka da kokwanto game da gaskiyar Musulunci, suna gaggawa wajen taimaka wa Yahudawa da Nasara, suna kare kansu da cewa su fa suna yin haka ne domin gudun kada wata musifa ta auko, a sami sauyin yanayi, kafirai su yi galaba a kan Musulmi. To idan har haka ya faru, su kam za su tsira; kafirai ba za su taɓa su ba, saboda taimakon da suka yi musu a baya. Sai Allah ya mayar musu da martani da cewa, tana yiwuwa Allah ya ba wa Musulmi nasara a kan Yahudawan da Nasaran, ko kuma

ya saukar da wata azabarsa da za ta halaka munafuƙai, ko kuma ya kunyata su a duniya, sai su wayi gari suna ta nadama marar amfani a gare su.
Idan kuma asirin munafuƙai ya tonu, sai muminai su yi ta mamakin cewa ashe da man waɗannan mutane maƙaryata ne, duk kuwa da irin rantse-rantsen da suke yi cewa, su ma kamar sauran muminai, sun yi imani, kuma suna son taimakon Musulunci da Musulmi. Amma ga shi yau ta bayyana manyan maƙaryata ne, don haka duk ayyukansu da suka yi a baya sun rushe, sun kuma tabbata cikin hasararru.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoratarwa game da yin ridda.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya buƙatar komai a wurin kowa. Da a ce duk mutane za su yi ridda su bar addinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), idan ya ga dama sai ya kawar da su baki ɗaya, ya kawo wasu mutanen masu son sa, masu taimakon addininsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙyamar masu ridda su bar Musulunci.

4. Wannan ayar ta [54] tana tabbatar da ƙaryar mabiya addinin Shi'a masu cewa bayan rasuwar Annabi (ﷺ) mafiya yawan sahabbai sun yi ridda. Wannan magana da a ce gaskiya ce, to da Allah ya kawo wasu mutane masu son sa sun yaƙe su, sun kawar da su kamar yadda ya yi alƙawari. To amma hakan bai faru ba, abin da yake nuna cewa wannan maganar ƙarya ce zalla.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son bawansa mai sauƙin kai da tawalu'u ga 'yan'uwansa muminai, yana ƙin duk wani mai girman kai, mai nuna isa ga 'yan'uwansa Musulmi. Don haka duk sa'adda mumini imaninsa ya ƙaru, to tawalu'unsa da sauƙin kansa ga 'yan'uwansa ma zai ƙaru.

6. Yana da kyau ga mumini ya nuna isarsa da izzarsa ga kafirai, kada ya yarda da ƙasƙanci a gabansu.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da rundunarsa waɗanda su ne masu riƙo da addininsa, masu taimaka wa addininsa da kira zuwa gare shi, wannan runduna ta Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ita ce mai yin rinjaye a ko da yaushe.

8. Yana da kyau ga duk wani mumini kada ya ji tsoron zargi a kan gaskiya, domin duk mai gaskiya yana da maƙiya daga mutane da aljanu, don haka tsoron zargi ba hujja ce a shari'a da za ta hana mutum faɗar gaskiya ba ko aiki da ita.

9. Wajibi ne mumini ya jiɓinci Allah ta hanyar riƙo da addininsa da taimaka wa addinin da tsayawa a kan gaskiya; ya kuma jiɓinci Manzon Allah (ﷺ) ta hanyar riƙo da sunnarsa da aiki da ita; ya kuma jiɓinci 'yan'uwansa muminai ta hanyar ƙaunar su da taimakon su da ba su kariya.

10. Riƙo da addinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ƙaunar juna tsakanin Musulmi da Musulmi yana daga cikin hanyoyin samun nasara a kan abokan gaba.

11. Tabbatar wa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) siffar so. Allah yana son bayinsa muminai, su ma suna son sa.

Suratul Ma’ida (54-56)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَن يَرۡتَدَّ مِنكُمۡ عَن دِينِهِۦ فَسَوۡفَ يَأۡتِي ٱللَّهُ بِقَوۡمٖ يُحِبُّهُمۡ وَيُحِبُّونَهُۥٓ أَذِلَّةٍ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَعِزَّةٍ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ يُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا يَخَافُونَ لَوۡمَةَ لَآئِمٖۚ ذَٰلِكَ فَضۡلُ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ٥٤ إِنَّمَا وَلِيُّكُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُمۡ رَٰكِعُونَ ٥٥ وَمَن يَتَوَلَّ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَإِنَّ حِزۡبَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلۡغَٰلِبُونَ ٥٦

54. Ya ku waɗanda suka yi imani, duk wanda ya yi ridda daga cikinku, ya bar addininsa, to (ya sani) Allah zai kawo waɗansu mutane da Yake son su suna son Sa, suna masu ƙasƙantar da kai ga muminai, suna masu nuna wa kafirai isa, suna yin jihadi don ɗaukaka kalmar Allah, kuma ba sa jin tsoron zargin wani mai zargi. Wannan falalar Allah ce da Yake bayar da ita ga wanda Ya ga dama. Kuma Allah Mayalwaci ne, Masani.

55. Allah ne kaɗai majiɓincin al’amarinku da Manzonsa da kuma waɗanda suka yi imani, waɗanda suke tsayar da salla, kuma suke bayar da zakka, suna kuma masu yin ruku’i.
56. Kuma duk wanda ya jiɓinci Allah da Manzonsa da waɗanda suka yi imani, to lalle rundunar Allah su ne masu rinjaye.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin halin wani rukuni na mutane masu yin ridda su bar addinin Musulunci, ko dai ta hanyar haɗa kai da Yahudawa da Nasara wajen yaƙar Musulunci da Musulmi, ko kuma ta wata hanyar daban. Allah ya bayyana cewa duk wanda ya yi ridda ya koma kafirci, to wannan riddar ba za ta cutar da addinin Allah ba, ba kuma zai iya cutar da Musulmi da ita ba. Hasali ma idan Allah ya ga dama zai iya maye gurbinsa da wasu mutane masu son Allah, shi ma yake son su, masu tausayin ‘yan’uwansu muminai, masu tawali’u gare su, kuma masu tsanani ga kafirai maƙiyansu, suna nuna musu isa saboda ɗaukakar addininsu, kuma suna yin jihadi da dukiyoyinsu da rayukansu, don su ga kalmar Allah ita ce a sama. Ba abin da yake hana su wannan aiki, domin ba sa tsoron wani mai zargi ya zarge su, ba kuma yardar wani suke nema ba sai yardar Allah shi kaɗai. Sannan sai Allah ya bayyana cewa duk waɗannan kyawawan halaye da ya ba wa muminai, falala ce daga gare shi wadda yake ba da ita ga wanda ya ga dama, domin shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mayalwaci ne, mai cikakken sani.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin mutanen da ya wajaba ga Musulmi su nisanci haɗa kai da su da taimaka musu, sai kuma ya bayyana waɗanda ya zama wajibi su jiɓince su, su nuna musu ƙauna. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne na farko, domin shi ne mai taimakon su a koyaushe mai jiɓintar lamarinsu. Jiɓintar Allah kuwa ita ce taimakon addininsa da taimakon mabiya addininsa. Sannan kuma da jiɓintar Manzonsa (ﷺ) wanda ta hanyarsa ne Allah ya fitar da mutane daga duhun kafirci zuwa ga hasken Musulunci. Shi kuma jiɓintar sa da taimakonsa shi ne riƙon addinin da Allah ya aiko shi da shi da taimakon sunnarsa da ba ta kariya da yaɗa ta. Sannan sai jiɓintar muminai masu tsai da salla yadda take, masu fitar da zakkar dukiyoyinsu, su ba da ita ga waɗanda suka cancanta, kuma su ne masu ƙasƙantar da kansu a gaban Mahaliccinsu Allah. Sannan ya bayyana sakamakon waɗanda suka jiɓinci Allah da Manzonsa da muminai da cewa su ne rundunar Allah, waɗanda kuma su ne masu samun galaba a koyaushe.
A ƙarƙashin wannan aya, mabiya addinin Shi’a suna da’awar cewa wannan ayar ta sauka ne game da Sayyadina Ali (Allah ya kara masa yarda), a lokacin da yana tsakiyar salla, ya yi ruku’u, sai wani mai bara ya zo yana bara, sai ya ciro zoben azurfa daga ɗan yatsansa ya ba shi sadaka, sai wannan ayar ta sauka. Suka ce ita wannan ayar wai tana nuna shugabancin Sayyadina Ali ne, wato shi ne ya cancanci ya zama halifan Manzon Allah (ﷺ) bayan cikawarsa, ba Sayyadina Abubakar (Allah ya kara masa yarda) ba. Wannan batu nasu ƙarya ne saboda dalilai kamar haka:
Na ɗaya: Ayar ƙarara tana magana ne a kan mutane da yawa, ba mutum ɗaya ba.

Na biyu: Da a ce yadda suka fassara ayar cewa Ali (Allah ya kara masa yarda) yana cikin halin ruku'u ne ya ba da zakka, da sai ya kasance ba wanda zai yi shugabanci sai wanda ya ba da sadaka yana tsakiyar ruku'u, don haka ma sauran Ahalul-baiti ba za su zama shugabanni ba, tun da ba a ruwaito sun ba da zakka a cikin halin ruku'u ba.
Na uku: Ana yin yabo ne a kan aikata wajibi ko mustahabbi. Mutum ya ba da zakka yana tsakiyar yin salla ba aiki ne na wajibi ko kuma mustahabbi ba, a wurin duk malaman Musulunci.
Na huɗu: Da a ce bayar da zakka sanda ake salla abu ne mai kyau, to da babu wani bambanci tsakanin wanda ya bayar yana cikin ruku'u da wanda ya bayar yana tsaye ko yana zaune; wanda ma zai bayar yana tsaye ko zaune sai ya fi wanda ya bayar yana ruku'u.
Na biyar: Sayyadina Ali (Allah ya kara masa yarda) zakka ba ta wajaba a kansa ba a zamanin Manzon Allah (ﷺ) domin ba shi da kuɗin da ya kai nisabin zakka a lokacin.
Na shida: Fitar da zakka da wata dukiya ba zobe ba ya fi fitar da zobe, domin da yawa daga cikin malamai suna ganin fitar da zobe ba ya isarwa a zakka.
Na bakwai: A bayaninsu sun ce, ya ba wa wani mai bara ne, alhali kuwa an fi yabon wanda zai bayar ba tare da an roƙe shi ba.
Na takwas: Ayar ta zo ne a cikin jerin gwanon ayoyi masu magana a kan hana jiɓintar kafirai da taimakon su da yin umarni a kan jiɓintar muminai da ƙaunar su da taimakon su, don haka ba maganar shugabanci ne ake yi a ayoyin ba. Kuma kalmar [الوِلَايَة] mai '*wau*'da wasali ƙasa ta sha bamban da kalmar [الوَلَايَة] mai '*wau'* da wasali sama. Ta farko ita ce da ma'anar shugabanci, wadda kuma ba ta zo a wannan ayar ba. Ta biyu ita ce da ma'anar ƙauna da jiɓinta, wadda ita ce ta zo a wannan ayar. Mabiya addinin Shi'a sun fi kowa saɓa wa wannan ayar, domin su ne masu haɗa kai da Yahudawa da Nasara wajen cutar da Musulmi da yaƙar su a kowane lokaci. [Dubi, Ibni Taimiyya, *Minhajus Sunnah*, Juzu'i na 2, Shafi na 30-32].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi da jan kunne a kan ƙawance da kafirai masu izgili da addinin Allah. Duk wani mutum mai kishin addininsa ba zai yarda da wanda yake ganin addininsa a matsayin abin wasa marar amfani ba.

2. Yahudawa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su ilimi, amma iliminsu bai amfane su da komai ba. Ilimi na gaskiya shi ne ilimin da yake sa tsoron Allah a zuciya.

3. Bayani a kan shar'anta kiran salla da tabbatar da shi a matsayin ibada da ake neman kusancin Allah da ita. Don haka kiran salla yana daga cikin ibadu masu falala.

4. Kula da tsayar da salla yana nuna cikar hankalin bawa, tozarta salla ko wasa da ita yana nuna tawayar hankalin mai aikata hakan.

5. Yahudawa suna jin haushin muminai saboda sun ƙi yarda su bi hanyarsu ta fasiƙanci. Wannan shi ne musabbabin gabar da take tsakaninsu.

6. Matsayin mutum a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne abin lura ba matsayinsa a wurin mutane ba. Idan bawa matsayinsa mai kyau ne a wurin Allah, to kar ya damu da yaya mutane suka ɗauke shi.

7. Yahudawan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da su birrai da aladu ba su hayayyafa ba, saboda hadisin da Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya kara masa yarda) ya ruwaito cewa: Wani mutum ya tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa, shin birrai da aladu su ne zurriyar waɗanda aka shafe halittarsu? Sai Annabi (ﷺ) ya ba shi amsa da cewa: "Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai halaka wasu mutane ba, ko ya yi

musu azaba, sannan ya sanya musu zuri’a. Kuma ko da can (kafin wannan azabar) akwai birrai da aladu.” [Muslim #2623].

8. Tabbatar wa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) siffar fushi. Yana yin fushi ga wanda ya ga dama yayin da ya saba masa.

Suratul Ma’ida (57-61)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ دِينَكُمۡ هُزُوٗا وَلَعِبٗا مِّنَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِكُمۡ وَٱلۡكُفَّارَ أَوۡلِيَآءَۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٥٧ وَإِذَا نَادَيۡتُمۡ إِلَى ٱلصَّلَوٰةِ ٱتَّخَذُوهَا هُزُوٗا وَلَعِبٗاۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَعۡقِلُونَ ٥٨ قُلۡ يَـٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ هَلۡ تَنقِمُونَ مِنَّآ إِلَّآ أَنۡ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبۡلُ وَأَنَّ أَكۡثَرَكُمۡ فَٰسِقُونَ ٥٩ قُلۡ هَلۡ أُنَبِّئُكُم بِشَرّٖ مِّن ذَٰلِكَ مَثُوبَةً عِندَ ٱللَّهِۚ مَن لَّعَنَهُ ٱللَّهُ وَغَضِبَ عَلَيۡهِ وَجَعَلَ مِنۡهُمُ ٱلۡقِرَدَةَ وَٱلۡخَنَازِيرَ وَعَبَدَ ٱلطَّٰغُوتَۚ أُوْلَٰٓئِكَ شَرّٞ مَّكَانٗا وَأَضَلُّ عَن سَوَآءِ ٱلسَّبِيلِ ٦٠ وَإِذَا جَآءُوكُمۡ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَقَد دَّخَلُواْ بِٱلۡكُفۡرِ وَهُمۡ قَدۡ خَرَجُواْ بِهِۦۚ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا كَانُواْ يَكۡتُمُونَ ٦١

57. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi waɗanda suke yin izgili da wasa da addininku, waɗanda aka bai wa Littafi tun kafinku, da kuma kafirai, a matsayin masoya, kuma ku kiyaye dokokin Allah, in har da gaske ku muminai ne.

58. Kuma idan kuka yi kiran salla, sai su ɗauke ta abin yi wa izgili da wasa. Suna yin hakan don su mutane ne da ba sa hankalta.

59. Ka ce: “Ya ku Ma’abota Littafi, shin kuna da abin da kuke ƙi a tare da mu ne? Sai fa cewa, mun yi imani da Allah da abin da aka saukar mana da abin da aka saukar kafinmu da kuma cewa, lalle yawancinku fasiƙai ne.”

60. Ka ce: “Shin ba na ba ku labarin sakamakon da ya fi wannan sharri a wurin Allah ba? Shi ne wanda Allah Ya la’anta, kuma Ya yi fushi da shi, kuma Ya mayar da wasu daga cikinsu birrai da aladu; kuma ya bauta wa gunki. Su waɗannan su ne matsayinsu ya fi sharri, kuma (su ne) suka fi ɓacewa daga tafarkin shiriya.”

61. Kuma idan suka zo muku, sai su ce: “Mun yi imani”, alhali kuwa haƙiƙa sun shigo da kafirci ne, kuma haƙiƙa sun fita da shi ne. Allah kuwa Shi ne Mafi sanin abin da suka kasance suna ɓoyewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana hana muminai su yi ƙawance da abota da maƙiyansu kafirai masu yin izgili ga addinin Musulunci da wasu ayyuka na ibada da ya ƙunsa, suna wulaƙanta su, suna ɗaukar su kamar abin wasa. Waɗannan mutane kuwa ana samun su daga cikin Yahudawa da Nasara da sauran kafirai. Sannan ya umarce su da su kiyaye dokokin Allah idan har sun kasance muminai ne su, to kada su yarda su aikata duk abin da aka hana su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir da irin izgilin da Yahudawa da Nasara suke yi wa muminai yayin da suka ji suna kiran salla, suna ɗaukar wannan ibada wani abin wasa, kuma ba komai ya sa suke yin haka ba sai don su mutane ne marasa hankali da ba su san girman Mahaliccinsu da hikimomin da suke ƙunshe cikin waɗannan ibadu da suke yi wa izgili ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya bayyana wa Ma’abota Littafi dalilin da ya sa suke gaba da shi da sahabbansa da sauran muminai, wato ba don komai ba sai don kawai sun yi imani da Allah, da Alƙur’anin da aka saukar musu, kuma sun yi imani da littafan Attaura da Linjila da aka

saukar gabaninsu. Hasali ma da yawa daga cikin Ma'abota Littafi fasiƙai ne, ba sa bin hanyar Allah ta gaskiya; wannan kuwa ba dalili ba ne da zai sa su riƙa kushe addinin Allah, suna izgili da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa Yahudawa masu kushe wa addinin Musulunci da ƙirƙira masa ƙarya iri-iri cewa, ai nasu addini ne mai mummunar makoma saboda cancanza shi da suka yi, har ta kai Allah ya la'ance su saboda yawan saɓonsu, ya yi fushi da su, ya ma mayar da wasu daga cikinsu birrai, wasu kuma aladu, wasu kuma suka dinga bauta wa Ɗagutu, wanda shi ne duk wani abu da bawa zai saki hanyar Allah saboda shi. To waɗannan su ne mafi sharrin mutane a duniya da lahira, ba muminai ba waɗanda suka tsare addininsu suna biyayya ga Allah da Manzonsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya dawo kan sukar waɗansu halaye na munafuƙai, wato ɗabi'ar ƙarya. Duk lokacin da suke tare da muminai, za su ce sun yi imani alhali ƙarya ce suke yi, suna nan riƙe da akidarsu ta kafirci, da ita ce suka shigo cikin muminai hakanan da ita suke fita su bar su, duk maganganun da suke yi su ba sa musu wani amfani. Allah masanin sarari da ɓoye shi ne mafi sanin abin da suke ɓoyewa, kuma zai yi musu sakayya a kansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi a kan girman zunubin mai gaggawa cikin saɓon Allah da ta'addanci da cin haramun. Kuma duk mai aikata haka ya yi kama da Yahudawa.

2. Girman nauyin da yake a kan malamai da masu karantarwa. Allah ya ɗora alhakin taɓarɓarewar rayuwar Yahudawa a kansu saboda sun yi shiru ba su fito sun hana su aikata saɓon Allah ba.

3. Bayanin ta'addancin Yahudawa har ga Mahaliccinsu Allah, ta yadda suka tuhumce shi da rowa da mako.

4. Tabbatar wa da Allah siffar hannaye biyu, bisa yadda ya dace da Zatinsa, ba tare da kwatance ba.

5. Bayanin yawan kyautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) marar iyaka ga bayinsa, kuma yana bayarwa ne ga wanda ya ga dama.

6. Haramcin yaɗa ɓarna a bayan ƙasa.

7. Bayanin ƙiyayyar da Allah ya jefa a tsakanin Yahudawa. Za a gan su kamar kansu a haɗe yake, amma zukatansu daban-daban suke.

8. Albishir ga Musulmi cewa Yahudawa ba za su yi galaba a kan Musulmi ba ko da kuwa sun haɗa kai wajen yaƙar su, domin duk sa'adda za su kunno wutar yaƙi Allah zai kashe ta.

Suratul Ma'ida (62-64)

وَتَرَىٰ كَثِيرًا مِّنْهُمْ يُسَٰرِعُونَ فِى ٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِ وَأَكْلِهِمُ ٱلسُّحْتَ ۚ لَبِئْسَ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٦٢﴾ لَوْلَا يَنْهَىٰهُمُ ٱلرَّبَّٰنِيُّونَ وَٱلْأَحْبَارُ عَن قَوْلِهِمُ ٱلْإِثْمَ وَأَكْلِهِمُ ٱلسُّحْتَ ۚ لَبِئْسَ مَا كَانُوا۟ يَصْنَعُونَ ﴿٦٣﴾ وَقَالَتِ ٱلْيَهُودُ يَدُ ٱللَّهِ مَغْلُولَةٌ ۚ غُلَّتْ أَيْدِيهِمْ وَلُعِنُوا۟ بِمَا قَالُوا۟ ۘ بَلْ يَدَاهُ مَبْسُوطَتَانِ يُنفِقُ كَيْفَ يَشَآءُ ۚ وَلَيَزِيدَنَّ كَثِيرًا مِّنْهُم مَّآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ طُغْيَٰنًا وَكُفْرًا ۚ وَأَلْقَيْنَا بَيْنَهُمُ ٱلْعَدَٰوَةَ وَٱلْبَغْضَآءَ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ كُلَّمَآ أَوْقَدُوا۟ نَارًا لِّلْحَرْبِ أَطْفَأَهَا ٱللَّهُ ۚ وَيَسْعَوْنَ فِى ٱلْأَرْضِ فَسَادًا ۚ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٦٤﴾

62. Kuma za ka ga yawancinsu suna yin gaggawa wajen aikin saƀo da ƙetare iyaka da kuma cin haramun. Lalle tir da abin da suka kasance suna aikatawa.

63. Me ya hana malamansu na Allah da masanansu ba su kwaƀe su daga yin maganar saƀo da cin haram ba? Tir da abin da suka kasance suna aikatawa.

64. Kuma Yahudawa suka ce: “Hannun Allah a ƙuƙunce yake.” To an ƙuƙunce hannayensu, kuma an la’ance su sakamakon abin da suka faɗa. Kuma ba haka ba ne. Hannayensa a shimfiɗe suke; Yana ciyarwa yadda Ya ga dama. Kuma abin da aka saukar maka daga wajen Ubangijinka lalle yana daɗa wa yawancinsu shisshigi da kafirci. Kuma Mun jefa gaba da ƙiyayya a tsakankaninsu har zuwa ranar tashin alƙiyama. Duk lokacin da suka yi yunƙurin rura wutar yaƙi, sai Allah Ya bice ta; kuma suna masu tafiya a bayan ƙasa suna aikata ƀarna. Allah kuwa ba ya son maƀarnata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabi (ﷺ) wani mummunan halin yawancin Yahudawa ne, wato yadda za ka gan su suna rige-rige wajen aikata saƀon Allah da shiga haƙƙoƙin mutane ta hanyar yi musu ta’addanci da cin dukiyarsu ba bisa gaskiya ba. Allah ya yi tir da irin wannan mummunan aikin nasu. Sannan ya bayyana cewa, me ya sa malamansu na Allah da masanan cikinsu ba su hana su saƀon Allah da cin dukiyar haramun ba? Allah ya sake yin tir da irin wannan hali na malaman Yahudawa da suke yin shiru ba sa faɗa musu gaskiya, ba sa hana su aikata munanan ayyuka. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata mummunar magana da Yahudawa suke furta masa, suna cewa, hannun Allah a ƙuƙunce yake, wato ba ya kyauta. Allah ya tsarkaka daga wannan mummunar maganar tasu. Allah ya mayar musu da martani da cewa su ne hannuwansu suke a ƙuƙunce, kuma an la’ance su a kan wannan furuci nasu, amma shi Allah hannayensa a shimfiɗe suke, koyaushe yana kyauta, yana baiwa yadda ya ga dama.

An karƀo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Lalle hannun Allah na dama a cike yake, abin da yake cikinsa kuma ba ya raguwa saboda bayarwa. Allah mai kyautar dare da rana ne. Shin kun ga abin da ya ciyar tun lokacin da ya halicci sammai da ƙasa? Abin da yake a hannunsa bai ragu ba.” [Bukhari #7419, da Muslim #993].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa Muhammadu (ﷺ) cewa, idan Yahudawa suka saurari Alƙur’anin da aka saukar maka, sai abin ya ƙara musu shisshigi da kafirci. Kuma ya bayyana cewa ya sanya gaba da ƙiyayya a tsakanin Yahudawa su kansu, kuma za su ci gaba da rayuwa a haka har zuwa tashin alƙiyama. Duk sa’adda suka kunna wutar yaƙi da muminai sai Allah ya kashe ta, daga nan sai gwiwowinsu su yi sanyi. Ko da kuwa sun tayar da wani yaƙi a cikin al’umma to sai Allah ya mayar da muguwar aniyarsu a kansu, su faɗa ramin muguntar da suka haƙa da hannuwansu. Suna gaggawar yaɗa ƀarna a bayan ƙasa ta hanyar saƀon Allah da yaƙi da Musulunci, kuma Allah ba ya son maƀarnata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya tuba daga aikata zunubai, Allah zai yi masa sakayya kashi biyu: A nan duniya Allah zai ba shi arziki sama da ƙasa; a lahira kuma Allah zai kankare masa zunubansa, ya kuma shigar da shi gidan Aljanna.

2. Ya halatta a kwaɗaitar da mutum a kan aikin ɗa’a da wani sakamako na duniya da Allah zai yi masa.

3. Imani shi ne ginshiƙin duk ayyuka na ƙwarai, shi ya sa aka fara ambaton sa.

4. Cikar adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Don haka duk wanda ya tuba daga kafirci, ya yi imani, to Allah zai yafe masa, ya saka masa da gidan Aljanna.

5. Bayanin yalwar rahamar Allah da falalarsa, don haka ya buɗe ƙofar tuba ga duk wani mai son ya tuba komai girman zunubinsa.

6. Bayanin cewa Ma'abota Littafi, bayan aiko da Annabi Muhammadu (ﷺ), ba za su shiga Aljanna ba, har sai sun yi imani da shi, sun karɓi Musulunci.

7. Wajibi ne a kan malamai su sanar da mutane addinin Allah, domin su ne magada annabawa, don haka dole ne a kansu su ba da haƙƙin wannan gado, wanda shi ne isar da shari'ar Allah.

8. Zukatan bayi gaba ɗaya a hannun Allah suke, shi ne yake jujjuya su yadda ya ga dama.

9. Abin la'akari ga Musulmi shi ne ya fahimci cewa babu wani abu na addini da Musulmi za su yi tinƙaho da shi, matuƙar ba su yi aiki da koyarwar Alƙur'ani ba.

10. Ɓoye wani ɓangare na shari'a daidai yake da ɓoye gaba ɗayanta.

11. Kaɗan ne daga cikin Ma'abota Littafi suke jin Alƙur'ani, su miƙa wuya, imaninsu ya ƙaru; yawancinsu sai dai ya ƙara musu shisshigi da kafirci.

12. Kafirci ma yana ƙaruwa, yana raguwa, kamar imani.

Suratul Ma'ida (65-68)

وَلَوْ أَنَّ أَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ ءَامَنُوا۟ وَٱتَّقَوْا۟ لَكَفَّرْنَا عَنْهُمْ سَيِّـَٔاتِهِمْ وَلَأَدْخَلْنَٰهُمْ جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ﴿٦٥﴾ وَلَوْ أَنَّهُمْ أَقَامُوا۟ ٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِم مِّن رَّبِّهِمْ لَأَكَلُوا۟ مِن فَوْقِهِمْ وَمِن تَحْتِ أَرْجُلِهِمْ ۚ مِّنْهُمْ أُمَّةٌ مُّقْتَصِدَةٌ ۖ وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ سَآءَ مَا يَعْمَلُونَ ﴿٦٦﴾ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ بَلِّغْ مَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ ۖ وَإِن لَّمْ تَفْعَلْ فَمَا بَلَّغْتَ رِسَالَتَهُۥ ۚ وَٱللَّهُ يَعْصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٦٧﴾ قُلْ يَٰٓأَهْلَ ٱلْكِتَٰبِ لَسْتُمْ عَلَىٰ شَىْءٍ حَتَّىٰ تُقِيمُوا۟ ٱلتَّوْرَىٰةَ وَٱلْإِنجِيلَ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْكُم مِّن رَّبِّكُمْ ۗ وَلَيَزِيدَنَّ كَثِيرًا مِّنْهُم مَّآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ طُغْيَٰنًا وَكُفْرًا ۖ فَلَا تَأْسَ عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٦٨﴾

65. Kuma in da a ce waɗanda aka bai wa Littafi sun yi imani, kuma sun kiyaye dokokin Allah, to lalle da Mun kankare musu zunubansu, kuma lalle da Mun shigar da su gidajen Aljanna na ni'ima.

66. Kuma da a ce sun tsaya a kan aiki da Attaura da Linjila da kuma abin da aka saukar musu daga Ubangijinsu, lalle da sun ci daga samansu da kuma ƙarƙashin ƙafafunsu. Daga cikinsu akwai wata al'umma madaidaiciya, (amma) kuma mafi yawa daga cikinsu, irin abin da suke aikatawa ya munana (matuƙa).

67. Ya kai wannan Manzo, ka isar da abin da aka saukar maka daga Ubangijinka; idan kuwa ba ka yi ba, to ba ka isar da saƙonsa ba. Allah kuwa Shi ne Yake kare ka daga (sharrin) mutane. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutanen da suke kafirai.

68. Ka ce: "Ya ku Ma'abota Littafi, ba kwa kan wani abu (na addinin gaskiya), har sai kun tsaya a kan yin aiki da Attaura da Linjila da kuma abin da aka saukar muku daga wajen Ubangijinku." Kuma abin da ake

saukar maka daga Ubangijinka tabbas yana ƙara wa yawancinsu shisshigi da kafirci. Don haka kada ka yi baƙin ciki dangane da (abin da yake samun) mutane kafirai.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana cewa, da a ce da gaske Yahudawa da Nasara sun yi imani, sun kiyaye dokokin Allah, to da Allah ya kankare musu laifukansu da suke yi, kuma da ya shigar da su Aljanna mai cike da ni'imomi. Da kuma a ce sun yi aiki da umarnin Allaha da haninsa da yake cikin Attaura da Linjila da Alƙur'ani, to da ya kwararo musu arziki mai ɗimbin yawa ta ko'ina, kamar ruwan sama, ya fitar musu da amfanin gona mai yawa a gonakinsu. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba duk Yahudawa ne da Nasara suka taru suka zama ɗaya ba; a cikinsu akwai mutanen kirki masu son gaskiya da aiki da ita, masu aikata abin da Allah ya wajabta musu, masu barin abin da ya hana su, su tsaya a kan haka; amma mafi yawa daga cikinsu mutanen banza ne, masu miyagun ayyuka.
Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya isar da duk saƙon da ya aiko shi da shi kada ya rage komai daga ciki; idan kuwa har bai yi hakan ba, to bai yi wa Allah biyayya ba wajen isar da saƙonsa ga mutane.

An karɓo daga A'isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: "Duk wanda ya faɗa maka cewa Annabi (ﷺ) ya ɓoye wani abu daga abin da Allah ya saukar masa, to haƙiƙa ya faɗi ƙarya. Allah yana cewa: "Ya kai wannan Manzo, ka isar da abin da aka saukar maka...." [Bukhari #4612].

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Na bar muku abin da idan kun riƙe shi ba za ku ɓace ba bayana, shi ne Littafin Allah, kuma za a yi muku tambaya game da ni, to wace amsa za ku bayar?" Sai sahabbai suka ce: "Za mu ba da shaidar cewa ka isar da saƙo, ka bayar da amana, kuma ka yi nasiha." Sai Annabi (ﷺ) ya ɗaga ɗan yatsansa sama, yana nuna mutane da shi yana cewa: "Ya Allah ka shaida, ya Allah ka shaida." har sau uku. [Muslim #1218].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwantar wa da Annabinsa hankali, da cewa zai ba shi kariya daga mutane, kada tsoron wani mahaluƙi ya hana shi isar da saƙon da aka aiko shi da shi. Lalle Allah ba ya shiryar da mutanen da suke kafirai ne. Ya kuma umarce shi da ya faɗa wa Ma'abota Littafi cewa, abin da suke da'awar suna bi na addini ƙarya ce kawai suke faɗa, matuƙar ba za su yi aiki da Attaura da Linjila da Alƙur'ani ba. Ya ce da yawa daga cikin Yahudawa idan suka ji karatun Alƙur'ani, babu abin da yake ƙara musu sai ƙetare iyaka da kafirci, don haka kada ransa ya ɓaci saboda kafircinsu, shi dai ya isar da saƙon Ubangijinsa kawai, shi kuma zai isar masa daga gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A wajen ba da sakamako Allah ba ya la'akari da nasabar mutum ko matsayinsa; yana la'akari ne da imaninsa da aikinsa na ƙwarai.

2. Duk mabiya kowane addini a yanzu ba za su shiga Aljanna ba har sai sun yi imani da Manzon Allah (ﷺ), sun karɓi Musuluncin da ya zo da shi.

3. Haɗarin da ke tattare da bin son zuciya da barin nassi na shari'a, domin yakan iya kai mutum ga kafirci.

4. Hatsarin da ke tattare da mai saɓon Allah ya sakankance a kan cewa babu wani abu na uƙubar Allah da zai same shi a sanadiyyar wannan saɓon da yake yi.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yafe wa bawa laifinsa komai girmansa, idan ya tuba ya koma gare shi.

Suratul Ma’ida (69-71)

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ هَادُواْ وَٱلصَّٰبِـُٔونَ وَٱلنَّصَٰرَىٰ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْـَٔاخِرِ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٦٩﴾
لَقَدْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ وَأَرْسَلْنَآ إِلَيْهِمْ رُسُلًا ۖ كُلَّمَا جَآءَهُمْ رَسُولٌۢ بِمَا لَا تَهْوَىٰٓ أَنفُسُهُمْ فَرِيقًا كَذَّبُواْ وَفَرِيقًا يَقْتُلُونَ ﴿٧٠﴾ وَحَسِبُوٓاْ
أَلَّا تَكُونَ فِتْنَةٌ فَعَمُواْ وَصَمُّواْ ثُمَّ تَابَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ ثُمَّ عَمُواْ وَصَمُّواْ كَثِيرٌ مِّنْهُمْ ۚ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِمَا يَعْمَلُونَ ﴿٧١﴾

69. Lalle waɗanda suka yi imani da waɗanda suke Yahudawa da Sabi’awa da Nasara, duk wanda ya yi imani da Allah da ranar ƙarshe, kuma ya yi aiki nagari, to babu jin tsoro a tattare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.
70. Lalle haƙiƙa Mun ɗauki alƙawari daga Bani-Isra’ila, kuma Muka aika musu da manzanni. Duk sa’adda wani manzo ya zo musu da abin da zukatansu ba sa so, sai su ƙaryata waɗansu kuma su riƙa kashe waɗansu.

71. Kuma sun zaci cewa, babu wata fitina da za ta auku, sai suka makance kuma suka kurumce, sannan Allah Ya karɓi tubansu, sannan kuma da yawa daga cikinsu suka sake makancewa da kurumcewa. Allah kuma Mai ganin abin da suke aikatawa ne.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa ƙofarsa a buɗe take ga duk mabiya kowane addini; idan har sun yi imani da abin da ya saukar musu, to zai karɓe su a fadarsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo Musulmi, al’ummar Annabi Muhammadu (ﷺ) da Yahudawa mabiya Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kafin a shafe addininsu da kuma Sabi’awa, waɗanda su kuma ƙungiyoyi ne daban-daban, amma a nan ana nufin waɗanda su ba Yahudawa ba ne, ba kuma Nasara ba, kuma ba mushirikai ba ba majusawa ba; suna dai riƙe da Tauhidi, wato kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da haramta zalunci da miyagun ayyuka, ba tare da suna bin wani addini ba. Da Nasara mabiya Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kafin a shafe addininsu. Waɗannan ƙungiyoyi huɗu, duk wanda a cikinsu ya yi imani da Allah da ranar lahira, ya yi aiki na ƙwarai, to ba za su ji tsoron abin da za su fuskanta ba a nan gaba, kuma ba za su yi baƙin ciki a kan abin da za su bari a nan duniya ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa ya yi alƙawari mai ƙarfi da Bani-Isra’ila a kan yin imani da Allah da aiki da abin da ya wajabta musu aiki da shi, sannan ya aiko musu da manzanni masu kiran su zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), amma sai ga su duk lokacin da wani manzo ya zo musu da abin da ya saba wa son zuciyarsu, sai su ƙaryata wasu manzannin, wasu kuma su kashe su, kuma a zatonsu ba wani abu na uƙuba da zai same su a kan wannan mummunan aiki nasu, don haka sai suka ci gaba da shisshigin su da zarmewarsu cikin saɓon Allah, suka makance da gangan, ba sa ganin gaskiyar da ake nuna musu, suka zama kuramen ƙarfi da yaji, ba sa jin gaskiyar da ake faɗa musu. Daga baya Allah ya yafe musu laifukansu; to amma sai da yawa daga cikinsu suka ƙara koma wa mummunan halinsu na farko, suka ci gaba da ɓarnarsu, suka sake makancewa, ba sa ganin gaskiya, suka kurumce, ba sa jin gaskiya. Allah kuma yana ganin duk abin da suke aikatawa, kuma zai yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nasara kafirai ne, har sai sun bar muguwar aƙidarsu ta cewa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ne ko ɗan Allah ne, sun kuma yi imani da Annabi Muhammadu (ﷺ).

2. Tsayar da hujja a kan masu yin shirka da Allah tare da cewa sun yarda da Rububiyyarsa, kuma sun yarda gumakansu ba su da wata rububiyya, ba sa ji, ba sa gani, ba sa amfanarwa, balle cutarwa.

3. Duk wanda ya yi imani da Tauhidin Rububiyya, to dole ne ya yi imani da Tauhidin Uluhiyya. Wato idan ya yarda Allah ne mahaliccin kowa da komai, to dole ya amince da cewa shi ne kaɗai ya cancanci a bauta masa.

4. Makomar bayi a lahira dai ɗayan biyu ce, ko dai gidan Aljanna ko kuma gidan wuta.

5. Shirka babban zalunci ne da ba kamarsa.

6. Dogaro a kan cewa wasu za su yi ceto ba tare da kyakkyawar aƙida ba, ba zai amfani bawa da komai ba ranar lahira.
7. Tabbatar da adalcin Allah. Wato ba zai yi wa wani azaba ba sai wanda ya doge a kan kafircinsa da saɓon Allah, bai tuba ba har ya mutu.

8. Buɗe ƙofar tuba ga Allah. Komai girman zunubin bawa idan ya tuba Allah zai karɓi tubansa.

Suratul Ma'ida (72-77)

لَقَدۡ كَفَرَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ مَرۡيَمَۖ وَقَالَ ٱلۡمَسِيحُ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبَّكُمۡۖ إِنَّهُۥ مَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ ٱلۡجَنَّةَ وَمَأۡوَىٰهُ ٱلنَّارُۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ أَنصَارٖ ٧٢ لَّقَدۡ كَفَرَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ ثَالِثُ ثَلَٰثَةٖۘ وَمَا مِنۡ إِلَٰهٍ إِلَّآ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۚ وَإِن لَّمۡ يَنتَهُواْ عَمَّا يَقُولُونَ لَيَمَسَّنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٧٣ أَفَلَا يَتُوبُونَ إِلَى ٱللَّهِ وَيَسۡتَغۡفِرُونَهُۥۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٧٤ مَّا ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ مَرۡيَمَ إِلَّا رَسُولٞ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِ ٱلرُّسُلُ وَأُمُّهُۥ صِدِّيقَةٞۖ كَانَا يَأۡكُلَانِ ٱلطَّعَامَۗ ٱنظُرۡ كَيۡفَ نُبَيِّنُ لَهُمُ ٱلۡأٓيَٰتِ ثُمَّ ٱنظُرۡ أَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٧٥ قُلۡ أَتَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَمۡلِكُ لَكُمۡ ضَرّٗا وَلَا نَفۡعٗاۚ وَٱللَّهُ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٧٦ قُلۡ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَا تَغۡلُواْ فِي دِينِكُمۡ غَيۡرَ ٱلۡحَقِّ وَلَا تَتَّبِعُوٓاْ أَهۡوَآءَ قَوۡمٖ قَدۡ ضَلُّواْ مِن قَبۡلُ وَأَضَلُّواْ كَثِيرٗا وَضَلُّواْ عَن سَوَآءِ ٱلسَّبِيلِ ٧٧

72. Lalle haƙiƙa waɗanda suka ce: "Lalle Allah Shi ne Almasihu ɗan Maryamu" sun kafirta. Shi kuwa Almasihu cewa ya yi: "Ya ku Bani-Isra'ila, ku bauta wa Allah Ubangijina kuma Ubangijinku. Lalle yadda al'amarin yake, duk wanda ya yi shirka da Allah, to haƙiƙa Allah Ya haramta masa shiga Aljanna, kuma makomarsa ita ce wuta, kuma azzalumai ba su da wasu mataimaka."

73. Lalle haƙiƙa waɗannan da suka ce: "Lalle Allah Shi ne na cikon (alloli) uku," sun kafirta. Babu kuwa wani abin bauta wa na gaskiya, sai abin bauta Ɗaya tal. Idan ba su bar abin da suke faɗa ɗin nan ba, lalle azaba mai raɗaɗi za ta shafi waɗanda suka kafirta daga cikinsu.

74. Shin yanzu ba za su tuba zuwa ga Allah ba, kuma su nemi gafararsa? Allah kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

75. Shi fa Almasihu ɗan Maryamu bai zamo ba face Manzo, wanda haƙiƙa manzanni sun shuɗe kafinsa. Mahaifiyarsa kuma Siddiƙa ce; shi da ita sun kasance suna cin abinci. Duba ka ga yadda Muke bayyana musu ayoyi, sannan ka sake dubawa, ta yaya ake kautar da su?

76. Ka ce: "Shin yanzu kwa riƙa bauta wa wani ba Allah ba, wanda ba ya mallakar cutarwa ko amfanarwa a gare ku; Shi kuwa Allah Shi ne Mai ji, kuma Masani?"

77. Ka ce: “Ya ku ma’abota Littafi, kada ku zurfafa a ckin lamarin addiniku (ku ƙara) abin da ba gaskiya ba, kuma kada ku bi soye-soyen zukatan waɗansu mutanen da suka riga suka ɓata tun a da can, kuma sun ɓatar da mutane da yawa, kuma sun ɓace daga madaidaiciyar hanya.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙara tabbatar da kafircin Nasara waɗanda suke da’awar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ne, alhalin shi bawansa ne kamar sauran mutane; an san mahaifiyarsa, an san asalinsa, kuma shi kansa bai ce musu shi Allah ne ba; ya kirawo su ne gaba ɗayansu zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, domin shi da su duka Allah ne Ubangijinsu. Ya kuma hana su haɗa Allah da wani, ya nuna musu cewa duk wanda ya kuskura ya yi shirka da Allah, kuma har ya mutu bai tuba ba, to fa shi da shiga Aljanna har abada, domin ba mai shigar ta sai wanda ya kaɗaita Allah; kuma makomarsa ita ce wutar Jahannama, inda ba wani mai taimakon sa ko ya cece shi daga wannan azabar.
Hakanan ya tabbatar da kafircin Nasara saboda mummunar aƙidarsu ta cewa abu uku ne suka haɗu suka yi Allah, wato Isa da mahaifiyarsa da kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Suka mayar da Allah ɗayan abu uku. Allah ya ba su amsa da cewa babu wani abu da ya cancanci bauta sai Allah shi kaɗai. Sannan ya nuna musu hatsarin wannan muguwar aƙida da cewa wallahi in har ba su tuba suka yi watsi da ita ba to sun tabbata kafirai; su kuwa kafirai za su ɗanɗani azaba ce mai tsananin gaske.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu wannan gargaɗin, sai kuma ya buɗe musu ƙofar samun rahamarsa, ya kirawo su zuwa ga tuba da neman gafara, domin shi Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu wata ƙaƙƙarfar hujja a kan cewa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifiyarsa ba alloli ne ba kamar yadda su suke faɗa; Shi Manzo ne daga cikin manzannin Allah da suka gabata waɗanda gaba ɗayansu bayin Allah ne.
Mahaifiyarsa kuma ƙololuwar matsayinta shi ne ita siddiƙa ce, wato ba ta kai ma matsayin annabiya ba, balle a ce mata Allah. Ta gaskata ayoyin Allah, ta yi imani da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sannan ƙari a kan haka, Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifiyarsa dukansu mutane ne suna cin abinci, ka ga ashe mabuƙata ne, Allah kuwa ba mabuƙaci ne ba. To idan haka ne, me ya sa za su yarda cewa su alloli ne, har ma su riƙa bautar su? Sannan ya ja hankalin mai karatu da cewa, ya dubi yadda Allah yake bayyana dalilai da hujjoji a kan rushe cewa Annabi Isa da mahaifiyarsa alloli ne ababen bauta, amma duk da haka ake karkatar da su daga gane gaskiya da fahimtar waɗannan ƙwararan dalilai.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ƙalubalanci waɗannan kafirai da cewa, me ya sa suke bauta wa wanin Allah, wanda bai mallaki cutarwa ko amfanarwa ba, kuma Allah shi ne mai ji masani? Ya kuma umarce shi da ya yi musu kashedi da wuce gona da iri a cikin sha’anin addininsu har su riƙa kai wasu annabawa matsayin Allah; kada kuma su riƙa bin son zuciyar shugabanninsu da manyansu da jahilan masu ibada a cikinsu, waɗanda sun riga sun ɓace, kuma sun ɓatar da mutane masu yawa, kuma sun saki miƙaƙƙiyar hanya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yin shiru a kan laifuffukan da suke faruwa cikin al’umma ba tare da tsawatarwa ba, yana haifar da uƙubar Allah.

2. Yin umarni da kyakkyawan abu da hana mummuna wajibi ne a kan al’umma.

3. Banu Isra’ila suna da daɗaɗɗen tarihi na saɓon Allah wanda har ya jawo musu la’ana.

4. An la’anci Banu Isra’ila a cikin manyan littafan Allah guda huɗu, a zamanin Annabi Musa da lokacin Annabi Dawud da lokacin Annabi Isa da kuma zamanin Annabi Muhammadu (ﷺ).

5. Akwai kafirai a cikin Banu Isra’ila tun gabanin aiko Annabi (ﷺ), kamar yadda akwai muminai daga cikinsu, irin su Hawariyyawa da mutanen nan saba’in da Annabi Musa ya zaɓa.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya zaluntar kowa, kuma ba ya yi wa wani azaba sai idan ya saɓa masa.

7. Tabbatar wa da Allah siffar fushi, kamar yadda ya dace da kamalarsa da girmansa.

8. Yin ƙawance da kafirai ko taimakon su a kan mumini ya saɓa wa imani da Allah da Manzonsa da littafansa.

Suratul Ma’ida (78-81)

لُعِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۢ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ عَلَىٰ لِسَانِ دَاوُۥدَ وَعِيسَى ٱبۡنِ مَرۡيَمَۚ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَواْ وَّكَانُواْ يَعۡتَدُونَ٧٨ كَانُواْ لَا يَتَنَاهَوۡنَ عَن مُّنكَرٖ فَعَلُوهُۚ لَبِئۡسَ مَا كَانُواْ يَفۡعَلُونَ٧٩ تَرَىٰ كَثِيرٗا مِّنۡهُمۡ يَتَوَلَّوۡنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۚ لَبِئۡسَ مَا قَدَّمَتۡ لَهُمۡ أَنفُسُهُمۡ أَن سَخِطَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ وَفِي ٱلۡعَذَابِ هُمۡ خَٰلِدُونَ٨٠ وَلَوۡ كَانُواْ يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلنَّبِيِّ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مَا ٱتَّخَذُوهُمۡ أَوۡلِيَآءَ وَلَٰكِنَّ كَثِيرٗا مِّنۡهُمۡ فَٰسِقُونَ٨١

78. An la’anci waɗanda suka kafirta daga cikin Bani-Isra’ila a bisa harshen Dawuda da kuma Isa ɗan Maryamu. Hakan kuwa saboda abin da suka riƙa yi ne na saɓo, kuma sun kasance suna ƙetare iyaka.

79. Sun kasance ba sa hana junansu wani mummunan aikin da suka yi. Lalle tir da irin abin da suka kasance suna aikatawa.

80. Za ka ga yawancinsu suna nuna ƙauna ga waɗanda suka kafirta. Lalle tir da irin abin da kawunansu suka gabatar, don kuwa Allah Ya yi fushi da su, kuma su masu dawwama ne cikin azaba.

81. Kuma da sun kasance suna imani da Allah da Annabi da abin da aka saukar masa, da ba su riƙe su a matsayin masoya ba, sai dai kuma yawancinsu fasiƙai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙara bayyana munanan halayen Banu Isra’ila, da cewa, Annabawa biyu daga cikin annabawansu sun la’ance su saboda kangarewarsu da yawan saɓon Allah da suke yi tare da danne haƙƙoƙin mutane, kuma duk da haka ba sa yi wa juna nasiha suna hana juna saɓon Allah. Sai Allah ya yi tir da irin wannan mummunan hali nasu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo labarin halin Yahudawa a Madina a zamanin Manzon Allah (ﷺ), yadda suka riƙa haɗa kai da kafiran Makka don su cutar da Musulmi. Kuma Annabi (ﷺ) yana ganin da yawa daga cikinsu suna ƙawance da mushirikai a kan wannan mummunar manufa. Allah ya yi tir da wannan mugun aiki nasu, wanda suka yi wa kawunansu guzuri da shi na zuwa lahira inda za su gamu da fushin Allah da kuma azabar wutar Jahannama wadda za su shige ta har abada. Da a ce Yahudawan da gaske sun yi imani da Allah da Annabi Muhammadu (ﷺ) da Alƙur’ani, to da ba su haɗa kai da kafirai ba, to amma yawancinsu fasiƙai ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa Yahudawa da mushirikai a wuri ɗaya a wannan ayar saboda sun yi tarayya a kan ƙiyayyarsu ga Musulmi. Yahudawa suna hassada ne a kan Annabi bai fito daga cikinsu

ba, su kuma mushirikai suna yi wa Annabi hassadar Allah ya ba shi annabta ba su ba, suna kuma yi wa Musulmi hassadar sun riga su fahimtar gaskiya da jefar da ƙarya, sannan kuma ga girman kai da yake damun su.

2. Ilimi yana amfanar har wanda ma ba Musulmi ne ba. Hakanan ita ma ibada takan tausasa zuciyar mai yin ta, ya zamo mai tausayi.

3. Kaskantar da kai yana daga cikin abubuwan da ke taimaka wa mutum game da fahimtar gaskiya, kamar yadda girman kai kan sanya shi bijire mata.

4. Zubar da hawaye yayin sauraron maganar Allah abu ne da yake nuna imanin bawa. Duk sa'adda mutum imaninsa ya ƙaru, to ƙaskantar da kansa ga Allah ma zai ƙaru.

5. Duk sa'adda mutum ya fahimci gaskiya, to imaninsa zai ƙaru, gaskiya kuma ta ratsa shi da wuri.

6. Wajibi ne a kan mutum ya guji ji-ji da kai saboda wani aikin alheri da ya yi har ya yanke hukuncin shi ɗan Aljanna ne, sai dai ya riƙa fata, yana kwaɗayin ya sami irin wannan sakamakon.

7. Zaɓin aboki nagari wani muhimmin al'amari ne a rayuwar Musulmi.

8. Kwaɗaitarwa a kan kyautatawa, domin yin haka ibada ce, kuma Allah yana saka wa masu kyautatawa.

Suratul Ma'ida (82-86)

*لَتَجِدَنَّ أَشَدَّ ٱلنَّاسِ عَدَٰوَةً لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱلۡيَهُودَ وَٱلَّذِينَ أَشۡرَكُواْۖ وَلَتَجِدَنَّ أَقۡرَبَهُم مَّوَدَّةً لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّا نَصَٰرَىٰۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّ
مِنۡهُمۡ قِسِّيسِينَ وَرُهۡبَانٗا وَأَنَّهُمۡ لَا يَسۡتَكۡبِرُونَ ٨٢ وَإِذَا سَمِعُواْ مَآ أُنزِلَ إِلَى ٱلرَّسُولِ تَرَىٰٓ أَعۡيُنَهُمۡ تَفِيضُ مِنَ ٱلدَّمۡعِ مِمَّا عَرَفُواْ مِنَ ٱلۡحَقِّۖ
يَقُولُونَ رَبَّنَآ ءَامَنَّا فَٱكۡتُبۡنَا مَعَ ٱلشَّٰهِدِينَ ٨٣ وَمَا لَنَا لَا نُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَمَا جَآءَنَا مِنَ ٱلۡحَقِّ وَنَطۡمَعُ أَن يُدۡخِلَنَا رَبُّنَا مَعَ ٱلۡقَوۡمِ
ٱلصَّٰلِحِينَ ٨٤ فَأَثَٰبَهُمُ ٱللَّهُ بِمَا قَالُواْ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٨٥ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ
بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ٨٦

82. Tabbas lalle za ka samu cewa, mutanen da suka fi tsananin gaba da waɗanda suka yi imani, su ne Yahudawa da waɗanda suke mushirikai. Kuma tabbas lalle za ka sami waɗanda suka fi kusanci wajen nuna ƙauna ga waɗanda suka yi imani, su ne waɗanda suka ce: "Lalle mu Nasara ne." Wannan kuwa saboda a cikinsu akwai malamai da masu yawan ibada, don kuma lalle su ba sa yin girman kai.

83. Kuma idan sun ji abin da aka saukar wa wannan Manzo, za ka ga idanunsu suna zubar da hawaye, saboda abin da suka gane na gaskiya; suna cewa: "Ya Ubangijinmu, mun yi imani, don haka Ka rubuta mu cikin masu shaidawa.

84. "Kuma me muke da shi da ba za mu yi imani da Allah da abin da ya zo mana na gaskiya ba, muna kuwa sa rai Ubangijinmu Ya shigar da mu cikin salihan bayi?"

85. Sai Allah Ya saka musu saboda abin da suka faɗa, da gidajen aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dauwama a cikinsu, kuma wannan shi ne sakamakon masu kyautatawa.
86. Waɗanda kuwa suka kafirta, kuma suka ƙaryata ayoyinmu, waɗannan su ne 'yan wuta.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana miyagun halayen Yahudawa da Nasara a ayoyin da suka gabata, a nan kuma sai ya yi bayanin cewa waɗanda suka fi kowa tsananin gaba ga muminai su ne Yahudawa da mushirikai, saboda tsananin ƙiyayyarsu da hassadarsu gare su. Sannan kuma waɗanda suka fi kusancin soyayya ga muminai su ne Nasara, saboda a cikinsu akwai malamai, akwai kuma masu bautar Allah, kuma ba sa girman kai game da karɓar gaskiya.
Wasu masana Tafsiri, kamar Ibn Jarir At-Tabari da Al-Wahidi da kuma Al-Baghawi suna ganin Nasara da aka ambata a nan su ne waɗanda suka musulunta daga cikinsu, kamar Najashi Sarkin Habasha (Allah ya kara masa yarda).
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa idan sun saurari karatun Alƙur'ani sai su riƙa zubar da hawaye, saboda sun fahimci cewa abin da ake karanta musu gaskiya ne, har ma suna cewa: "Ya Ubangijinmu, mun yi imani, don haka ka rubuta mu tare da Annabi (ﷺ) da al'ummarsa." Suna ƙarawa da cewa: "Me zai hana mu yin imani da Allah da abin da ya zo mana ta hanyar Manzon Allah (ﷺ) na Alƙur'ani mai shiryarwa zuwa ga gaskiya? Kuma muna fata a dalilin wannan imanin namu Allah ya haɗa mu da mutanen kirki." To saboda imanin da suka yi da gaskiyar da suka faɗa sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu sakayya da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, kuma za su zauna a cikinsu zama na har abada. Wannan sakamako ne na wanda ya kyautata bautar Ubangijinsa, kuma ya kyautata wa mutane. Amma wanda ya kafirta, ya ƙaryata ayoyin Allah, to waɗannan su ne mazauna gidan wutar Jahannama har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mahalicci mai arzutawa, don haka shi ne kaɗai yake da haƙƙin halattawa da haramtawa, duk wanda ya ba wa kansa wannan haƙƙi, to ya shiga iyakokin Ubangiji.

2. Jan hankalin malaman shari'a a kan su yi taka-tsantsan wajen bayanin halaccin abu ko haramcinsa, matuƙar ba suna da ƙwaƙƙwaran dalili daga Allah da Manzonsa ba.

3. Bayanin baiwar Allah da ni'imarsa ga bayinsa, inda ya halatta musu kyawawan abubuwa; da ya ga dama da sai ya haramta mana su, kamar yadda ya haramta wasu abubuwa ga Banu Isra'ila saboda zaluncinsu da yawan saɓon Allah da suke yi.

4. Tabbatar da siffar 'soyayya' ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Allah yana son bayinsa masu taƙawa, yana kuma ƙin masu saɓa masa.

5. Arziƙin kowa da komai yana wajen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka); shi ne mai ba wa kowa rabonsa, don haka zafin nema ba shi ne yake kawo samu ba, sai dai bawa ya yi riƙo da sababi kamar yadda shari'a ta nuna.

6. Imani da Allah ne yake haifar da taƙawa. Duk mai imani da Allah, to shi ne mai kiyaye dokokin Allah. Bawa yana rasa taƙawa ne ko dai saboda babu imani gaba ɗaya tare da shi, ko kuma saboda ƙarancin imaninsa.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da ci da sha, sannan ya kawo umarni da taƙawa, wannan yana nuna dole ne bawa ya haɗa tsakanin haƙƙoƙin jiki da na ruhi, da haka ne bawa yake samun kamala.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana la'akari da ƙudurin zuciya, wato niyya, a cikin ayyukan bayinsa.

9. Jan hankali game da yawan rantsuwa. Ya dace mumini ya kiyaye harshensa daga yawan rantse-rantse.

Suratul Ma’ida (87-89)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُحَرِّمُواْ طَيِّبَٰتِ مَآ أَحَلَّ ٱللَّهُ لَكُمۡ وَلَا تَعۡتَدُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُعۡتَدِينَ ٨٧ وَكُلُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ حَلَٰلٗا طَيِّبٗاۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِيٓ أَنتُم بِهِۦ مُؤۡمِنُونَ ٨٨ لَا يُؤَاخِذُكُمُ ٱللَّهُ بِٱللَّغۡوِ فِيٓ أَيۡمَٰنِكُمۡ وَلَٰكِن يُؤَاخِذُكُم بِمَا عَقَّدتُّمُ ٱلۡأَيۡمَٰنَۖ فَكَفَّٰرَتُهُۥٓ إِطۡعَامُ عَشَرَةِ مَسَٰكِينَ مِنۡ أَوۡسَطِ مَا تُطۡعِمُونَ أَهۡلِيكُمۡ أَوۡ كِسۡوَتُهُمۡ أَوۡ تَحۡرِيرُ رَقَبَةٖۖ فَمَن لَّمۡ يَجِدۡ فَصِيَامُ ثَلَٰثَةِ أَيَّامٖۚ ذَٰلِكَ كَفَّٰرَةُ أَيۡمَٰنِكُمۡ إِذَا حَلَفۡتُمۡۚ وَٱحۡفَظُوٓاْ أَيۡمَٰنَكُمۡۚ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٨٩

87. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku haramta kyawawan abubuwan da Allah Ya halatta muku, kuma kada ku ƙetare iyaka. Lalle Allah ba Ya son masu ƙetare iyaka.
88. Kuma ku ci daga abin da Allah Ya arzuta ku da shi, wanda yake halal, mai daɗi. Kuma ku kiyaye dokokin Allah Wanda kuke yin imani da Shi.

89. Allah ba zai kama ku da yasassun rantse-rantsenku ba, sai dai Yana kama ku ne da laifin abin da kuka ƙudurce na rantsuwa; to kaffararsa ita ce ciyar da miskinai goma daga matsakaicin abin da kuke ciyar da iyalinku ko kuma tufatar da su ko ‘yantar da bawa; wanda kuwa bai sami iko ba, to sai ya yi azumin kwana uku. Wannan shi ne kaffarar rantsuwarku, in kun yi rantsuwa. Kuma ku kiyaye rantse-rantsenku. Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyinsa don ku zamo masu godiya.

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana kira ne ga muminai kada su haramta wa kansu kyawawan abubuwa da Allah ya halatta musu, kuma kada su tsallake halal su auka wa haram, domin Allah ba ya son masu ƙetare iyakokinsa.

An karɓo daga Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Usman ɗan Maz’un (Allah ya kara masa yarda) ya yi niyyar ya ƙaurace wa aure, sai Manzon Allah (ﷺ) ya hana shi. Da a ce hakan ya halatta da mun fiɗiye kawunanmu.” [Bukhari #5073, da Muslim #1402].

An karɓo daga Anas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Wasu mutane su uku sun je gidajen matan Annabi (ﷺ) suna tambaya game da ibadarsa. Lokacin da aka faɗa musu yadda yake ibada, sai suka ga kamar ta yi musu kaɗan, sai suka ce: “Ina za mu haɗa kawunanmu da Manzon Allah (ﷺ), alhali shi Allah ya riga ya gafarta masa abin da ya gabata na zunubinsa da abin da ya jinkirta?” Sai ɗaya daga cikinsu ya ce: “Ni dai zan yi ta yin sallar dare har abada.” Ɗayan kuma sai ya ce: “Ni kuma zan yi ta azumi har abada ba zan ajiye ba.” Shi kuma na ukunsu sai ya ce: “Ni kuma zan ƙaurace wa mata, ba zan yi aure ba har abada.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya same su sai ya ce: “Ku ne masu faɗar maganganu iri kaza da kaza? Wallahi ni na fi ku tsoron Allah, kuma na fi ku taƙawa, tare da haka ina azumi ina sha, ina sallar dare ina kuma barci, kuma ina auren mata, don haka duk wanda ya ƙyamaci sunnata to ba ni ba shi.” [Bukhari #5063, da Muslim #1401].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su ci arziki na halal mai kyau wanda ya ba su shi kyauta, kuma su kiyaye dokokin Allah wanda da shi ne suka yi imani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da cewa ba ya kama mutane da yasasshiyar rantsuwa, ita ce rantsuwar da mutum yake yi ba da niyya ba; yana kama mutum ne da rantsuwar da ya ƙuduri niyya a kanta. Idan mutum ya yi rantsuwa sannan ya warware ta, to zai yi kaffara kamar haka:
• Ciyar da mabuƙata goma daga matsakaicin abincin da yake ciyar da iyalinsa, ko ya tufatar da su, ko ya ‘yanta bawa ko baiwa.

• Idan bai sami ikon ɗaya daga cikin ukun ba, to sai ya yi azumin kwanaki uku.Wannan shi ne kaffarar wanda ya warware rantsuwarsa.
Sai kuma ya umarci muminai da su kiyaye rantse-rantsensu watau su guji rantsuwa a kan ƙarya, su bar yawaita rantsuwa, sannan su daina yin rantsuwa suna warware ta, sai fa idan ya kasance yin hakan wani alheri ne, to idan sun warware ta sai su yi kaffarar rantsuwa, kamar yadda aka ambata. Kamar haka ne Allah yake bayanin ayoyinsa filla-filla ga bayinsa domin su gode masa a bisa hakan.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kowacce irin giya haramun ce. Hakanan duk wani kayan maye haramun ne.

2. Kowacce irin caca haramun ce, kuma komai ƙanƙantar kuɗin da za a sanya a cikinta.
3. Babu wani saɓon Allah mafi girma da muni kamar saɓon da yake jefa mutum cikin ayyukan Shaiɗan da tarkonsa, yake kuma haifar da adawa da ƙiyayya tsakanin Musulmi, yake kuma hana ambaton Allah da yin salla.

4. Duk abin da yake haɗa gaba da ƙiyayya tsakanin Musulmi ko yake hana bawa ambaton Allah, to wannan abu yana daga cikin ayyukan Shaiɗan. Ana ambaton Allah ne da zuciya da harshe da kuma gaɓoɓi.

5. Duk sa’adda bawa ya ji salla tana yi masa nauyi da wahala, to ya sani wannan daga Shaiɗan ne.

6. Bijirewar mutane daga abin da Annabi (ﷺ) ya yi umarni da shi ba zai cutar da shi da komai ba, domin shi aikinsa isar da saƙo ne. Hakanan bijirewar mutane ga kowane mai kira zuwa ga Allah ba zai cutar da shi da komai ba. Don haka kada ya yi baƙin ciki daga abin da zai gani na bijirewar masu bijirewa, ko taurin kan masu taurin kai.

7. Falalar ihsani, wato kyautayi. Kyautayi ga Allah shi ne mutum ya bauta masa kamar yana ganin sa, kyautayi ga mutane kuwa shi ne mutum ya taimaka wa ɗan’uwansa da dukiyarsa ko da matsayinsa.

8. Haramcin gumaka. Gunki shi ne duk wani abu da za a ajiye domin bautar sa, da ko mene ne aka yi shi.

9. Biyayya ga Annabi (ﷺ) tana cin gashin kanta ne, don haka duk abin da ya yi umarni da shi dole ne mu karɓe shi, ko da bai zo a Alƙur’ani ba.

10. Shiryar da mutane har su karɓi gaskiya ba a hannun Annabi (ﷺ) yake ba; wannan aikin Allah ne shi kaɗai. Aikin Manzon Allah (ﷺ) shi ne isar da saƙo.

Suratul Ma’ida (90-93)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡخَمۡرُ وَٱلۡمَيۡسِرُ وَٱلۡأَنصَابُ وَٱلۡأَزۡلَـٰمُ رِجۡسٞ مِّنۡ عَمَلِ ٱلشَّيۡطَـٰنِ فَٱجۡتَنِبُوهُ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٩٠ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱلشَّيۡطَـٰنُ أَن يُوقِعَ بَيۡنَكُمُ ٱلۡعَدَٰوَةَ وَٱلۡبَغۡضَآءَ فِي ٱلۡخَمۡرِ وَٱلۡمَيۡسِرِ وَيَصُدَّكُمۡ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَعَنِ ٱلصَّلَوٰةِۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّنتَهُونَ ٩١ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَٱحۡذَرُواْۚ فَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا عَلَىٰ رَسُولِنَا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٩٢ لَيۡسَ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّـٰلِحَـٰتِ جُنَاحٞ فِيمَا طَعِمُوٓاْ إِذَا مَا ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّـٰلِحَـٰتِ ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّأَحۡسَنُواْۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٩٣

90. Ya ku waɗanda suka yi imani, ita dai giya da caca da gumaka da kibau na neman sa'a, ba komai ba ne face ƙazanta daga aikin Shaiɗan, don haka ku nisance su domin ku sami rabauta.

91. Abin da kawai Shaiɗan yake nufi shi ne, ya jefa gaba da ƙiyayya a tsakankaninku, ta hanyar giya da caca, kuma ya hana muku ambaton Allah da yin salla. Shin ko kun hanu?

92. Kuma ku bi Allah, kuma ku bi wannan Manzon, kuma ku yi hattara. Idan kuka juya baya, to ku sani abin da kawai yake kan Manzonmu shi ne isar da saƙo filla-filla.

93. Babu wani laifi a kan waɗanda suka yi imani, kuma suka yi aiki nagari cikin abin da suka taɓa sha (na giya a baya), in dai sun yi taƙawa, kuma sun yi imani, kuma sun aikata aiki nagari, sannan suka yi taƙawa da imani, sannan suka yi taƙawa kuma suka kyautata. Kuma Allah Yana son masu kyautatawa.
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa bayinsa muminai cewa giya da caca da gumakan da ake bauta wa ba Allah ba da kibau da ake neman sa'a da su, dukkansu ayyukan Shaiɗan ne, shi ne yake ƙawata su a idanun wasu mutane don ya hana su samun rabo a wurin Allah.
Abin da ake nufi da kibau na neman sa'a shi ne, a lokacin jahiliyya Larabawa sun saba idan ɗayansu zai yi tafiya ko zai yi wani aiki, to sai ya shirya wasu kibau guda uku, ta farko an rubuta a kanta cewa: "Aikata", ɗaya kuwa an rubuta mata: "Kada ka aikata", ta ukun kuma ba a rubuta mata komai ba. Wasu kuma suka ce abin da aka rubuta a kibiyar farko: "Ubangijina ya umarce ni", ta biyun kuma: "Ubangijina ya hana ni", ta ukun ba a rubuta komai a jikinta ba. To sai ya karkaɗa waɗannan kibau uku, idan mai ɗauke da umarni ta fito, sai ya aikata abin da ya yi niyya, idan kuwa mai hanawa ce ta fito, sai ya fasa abin da ya yi niyya, idan kuwa marar rubutu ce a jiki ta fito, to sai ya sake kaɗawa har sai ɗaya daga cikin biyun nan (masu rubutun a jikinsu) ta fito. To shi ne Allah ya hana su irin wannan mummunan aikin.
Duka waɗannan laifuka guda uku da aka ambata masu muni ne da ya wajaba duk masu hankali su nisance su, saboda huɗubar Shaiɗan ne, wanda ba ya son ya ga bayi sun rabauta a duniya da lahira.
Manufar Shaiɗan har kullum ita ce ya haddasa adawa da ƙiyayya a tsakanin muminai ta hanyar giya da caca, saboda duk wanda ya sha giya ya bugu, ba abin da zai hana shi cutar da 'yan'uwansa cutarwar da za ta iya kaiwa ga kisa. Wanda ya shiga caca kuma zai iya hasarar duk dukiyarsa har ya shiga jin haushin abokin cacarsa, gaba da ƙiyayya ta shiga tsakaninsu.
Hakanan yana daga cikin miyagun manufofin Shaiɗan, ya hana ambaton Allah da tsayar da salla ta hanyar giya da caca. To idan muminai sun fahimci waɗannan illoli da ke cikin waɗannan miyagun ayyuka, to shin za su hanu daga aikata su ko kuwa a'a?

An karɓo daga Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: "Na zo wurin wata jama'a ta mutanen Makka masu hijira da mutanen Madina Al-Ansar, sai suka ce mini: "Zo mu je mu ba ka abinci, mu shayar da kai giya." Wannan tun kafin a haramta shan giya ne. Ya ce: "Sai na same su a cikin wani lambu, sai na samu sun tanadi gasasshen kan raƙumi da tulu na giya." Ya ce: "Sai na ci na ƙoshi, na sha giya, sai na yi magana a kan Muhajiruna mutanen Makka da kuma Al-Ansar mutanen Madina, sai na ce: "Al-Muhajiruna sun fi Al-Ansar." Da jin haka sai wani mutum ya ɗaga ƙashin dasashin haƙoran raƙumin ya dake ni da shi, har ya yi mini rauni a hanci. Sai na zo na faɗa wa Manzon Allah (ﷺ) abin da ya faru. To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar ta 91 a kan wannan abu da ya faru." [Muslim #1748].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa da su yi masa ɗa'a, kuma su yi wa Manzonsa (ﷺ) ɗa'a, kuma su guji saba wa umarnin Allah da Manzonsa, idan kuwa sun bijire ne, to su sani cewa isar da saƙo ne kawai a kan Manzo (ﷺ), amma uƙuba ga wanda ya bijire wannan aikin a wurin Allah yake.
Sai kuma ya bayyana cewa waɗanda suka yi imani, suka yi aiki nagari, ba su da wani laifi a kan abin da suka sha ko suka ci wanda Allah ya haramta, idan sun yi haka ne kafin a saukar da haramcinsa ko kafin su

san haramun ne, idan har sun nisanci abin da Allah ya haramta, kuma sun yi imani da Allah, sun yi ayyuka nagari, sannan suka ɗore a kan nisantar abin da Allah ya haramta da yin imani da Allah, sannan suka kuma doge a kan nisantar haramun har suka kai matakin ihsani, wato kyautayi, Allah kuwa yana son bayinsa masu kyautatawa.

An karɓo daga Anas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Na kasance ni ne mai shayar da mutane giya a gidan Abu Ɗalha, a lokacin suna yin giya ne da niƙaƙken dabino. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya umarci mai shela ya yi shela cewa, an haramta giya. Sai Abu Ɗalha ya ce da ni: “Fita waje ka kwarar da ita.” Sai na fita na kwarar da ita, har ta riƙa gudana a hanyoyin Madina. Sai wasu mutane suka riƙa cewa: “Ga shi an kashe wasu mutane da giya a cikinsu.” Sai Allah ya saukar da wannan ayar ta 93.” [Bukhari #2464, da Muslim #1980].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan jarrabi bayinsa ne ta hanyar hore musu wasu hanyoyin saɓo, don ya tantance wanda yake tsoron sa da gaske.

2. Falalar sahabban Manzon Allah (ﷺ), domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jarrabe su da abubuwan farauta yayin da suke cikin Harami, kuma sun ci wannan jarrabawar, hakan ya nuna suna jin tsoron Allah ba tare da sun gan shi ba, saɓanin Yahudawa da Allah ya jarrabe su da hana su kamun kifi ranar Asabar, amma ba su ci wannan jarrabawar ba, kamar yadda ya yi bayani a *Suratul A’arafi,* aya ta 163-166.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haramta yin farauta a halaye biyu: Lokacin da maniyyacin hajji ko umara ya ƙulla niyya; da lokacin da yake cikin Harami, wato Makka da kewayenta, ko da kuwa ba cikin ihrami yake ba. Allah ya yi haka ne don girmama ɗakin Ka’aba.

4. Hukuncin wanda ya yi farauta da gangan bayan an hana shi, shi ne kamar haka:
• Ya yanka wata dabba ta gida mai kama da dabbar daji da ya farauta. Mutum biyu muminai adalai su ne za su tantance dabbar da zai yanka. Zai yi yankan ne a Haramin Makka, ya raba naman ga matalauta.
• Ko kuma ya ciyar da miskinai abincin da kuɗinsa yake daidai da kuɗin dabbar da ya farauta, ko kuma dabbar da take kama da ita.
• Ko ya yi azumi na adadin matalautan da zai ciyar.

Suratul Ma’ida (94-96)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَيَبۡلُوَنَّكُمُ ٱللَّهُ بِشَيۡءٖ مِّنَ ٱلصَّيۡدِ تَنَالُهُۥٓ أَيۡدِيكُمۡ وَرِمَاحُكُمۡ لِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ مَن يَخَافُهُۥ بِٱلۡغَيۡبِۚ فَمَنِ ٱعۡتَدَىٰ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَلَهُۥ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٩٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقۡتُلُواْ ٱلصَّيۡدَ وَأَنتُمۡ حُرُمٞۚ وَمَن قَتَلَهُۥ مِنكُم مُّتَعَمِّدٗا فَجَزَآءٞ مِّثۡلُ مَا قَتَلَ مِنَ ٱلنَّعَمِ يَحۡكُمُ بِهِۦ ذَوَا عَدۡلٖ مِّنكُمۡ هَدۡيَۢا بَٰلِغَ ٱلۡكَعۡبَةِ أَوۡ كَفَّٰرَةٞ طَعَامُ مَسَٰكِينَ أَوۡ عَدۡلُ ذَٰلِكَ صِيَامٗا لِّيَذُوقَ وَبَالَ أَمۡرِهِۦۗ عَفَا ٱللَّهُ عَمَّا سَلَفَۚ وَمَنۡ عَادَ فَيَنتَقِمُ ٱللَّهُ مِنۡهُۚ وَٱللَّهُ عَزِيزٞ ذُو ٱنتِقَامٍ ٩٥ أُحِلَّ لَكُمۡ صَيۡدُ ٱلۡبَحۡرِ وَطَعَامُهُۥ مَتَٰعٗا لَّكُمۡ وَلِلسَّيَّارَةِۖ وَحُرِّمَ عَلَيۡكُمۡ صَيۡدُ ٱلۡبَرِّ مَا دُمۡتُمۡ حُرُمٗاۗ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِيٓ إِلَيۡهِ تُحۡشَرُونَ ٩٦ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَيَبۡلُوَنَّكُمُ ٱللَّهُ بِشَيۡءٖ مِّنَ ٱلصَّيۡدِ تَنَالُهُۥٓ أَيۡدِيكُمۡ وَرِمَاحُكُمۡ لِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ مَن يَخَافُهُۥ بِٱلۡغَيۡبِۚ فَمَنِ ٱعۡتَدَىٰ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَلَهُۥ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٩٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقۡتُلُواْ ٱلصَّيۡدَ وَأَنتُمۡ حُرُمٞۚ وَمَن قَتَلَهُۥ مِنكُم مُّتَعَمِّدٗا فَجَزَآءٞ مِّثۡلُ مَا قَتَلَ مِنَ ٱلنَّعَمِ يَحۡكُمُ بِهِۦ ذَوَا عَدۡلٖ مِّنكُمۡ هَدۡيَۢا بَٰلِغَ ٱلۡكَعۡبَةِ أَوۡ كَفَّٰرَةٞ طَعَامُ مَسَٰكِينَ أَوۡ عَدۡلُ ذَٰلِكَ

صِيَامًا لِّيَذُوقَ وَبَالَ أَمۡرِهِۦۗ عَفَا ٱللَّهُ عَمَّا سَلَفَۚ وَمَنۡ عَادَ فَيَنتَقِمُ ٱللَّهُ مِنۡهُۚ وَٱللَّهُ عَزِيزٞ ذُو ٱنتِقَامٍ ٩٥ أُحِلَّ لَكُمۡ صَيۡدُ ٱلۡبَحۡرِ وَطَعَامُهُۥ مَتَٰعٗا لَّكُمۡ وَلِلسَّيَّارَةِۖ وَحُرِّمَ عَلَيۡكُمۡ صَيۡدُ ٱلۡبَرِّ مَا دُمۡتُمۡ حُرُمٗاۗ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِيٓ إِلَيۡهِ تُحۡشَرُونَ ٩٦

94. Ya ku waɗanda suka yi imani, lalle Allah zai jarrabe ku da wani abu na farauta, wanda hannayenku da masunku za su kai gare shi, don Allah Ya bayyana wanda yake jin tsoron Sa alhalin bai gan Shi ba. Don haka duk wanda ya ƙetare iyaka bayan haka, to lalle yana da azaba mai raɗaɗi.

95. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kashe abin farauta alhali kuna cikin Harami. Duk kuwa wanda ya kashe shi daga cikinku da gangan, to sakamakonsa shi ne (ya bayar) da kwatankwacin abin da ya kashe cikin dabbobin gida; waɗanda za su yi hukunci da wannan su ne mutum biyu adalai a cikinku, a matsayin hadaya wadda za ta isa Ka'aba, ko kuma ya yi kaffarar ciyar da miskinai, ko kuma ya yi azumi na kwatankwacin haka, don ya ɗanɗani kuɗar lamarinsa. Allah Ya yi afuwa dangane da abin da ya wuce. Duk kuwa wanda ya sake komawa, to Allah zai yi masa uƙuba. Kuma Allah Mabuwayi ne, Ma'abocin uƙuba.
96. An halatta muku yin farautar naman ruwa da abincin cikinsa, don jin daɗi a gare ku da kuma matafiya; amma an haramta muku farautar naman daji matuƙar kuna cikin Harami. Kuma ku kiyaye dokokin Allah Wanda zuwa gare Shi za a tattara ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa muminai cewa zai jarrabe su, lokacin da suke sanye da Harami na hajji ko na umara, da wani abin farauta wanda za su iya kamawa da hannuwansu ko su farauce shi da masunsu. Allah zai yi musu wannan jarrabawar ne don ya tantance mai jin tsoron sa duk da cewa ba ya ganin sa ido-da-ido, ko kuma ana nufin wanda yake tsoron Allah duk da ba ya cikin jama'a, wato yana shi kaɗai. Duk wanda ya ƙetare iyakokin Allah da dokokin da ya gindaya a kan sha'anin farauta, ya yi farauta alhali yana sanye da Harami, ko yana cikin Harami, to ya saɓa wa shari'a, kuma zai gamu da azaba mai raɗaɗi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana hukuncin kashe abin farauta ga masu sanye da Harami, ko suke cikin yankin Harami, da gangan da cewa, wajibi ne su yanka wata dabba mai kama da irin wadda suka kashe, kuma za a sami mutum biyu ne muminai adalai waɗanda za su kwatanta irin dabbar da zai yanka. Kuma sai ta je Haramin Makka, a can ne zai yanka ta, ya raba wa mabuƙata namanta, ko kuma ya yi kaffara ta hanyar ciyar da miskinai, ko kuma in bai ɗauki wannan ba, to ya yi azumi a madadin kowane miskini da zai ciyar. Allah ya yi wannan hukunci ne domin wanda ya saɓa wa wannan umarni ya ɗanɗani uƙubar laifin da ya yi. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wani nau'i na rahamarsa ga bayinsa, watau afuwar da ya yi musu ga abin da ya riga ya wuce kafin wannan haramci, to amma fa duk wanda ya sake aikata wannan laifi bayan ya san hukuncinsa, to Allah zai yi masa uƙuba. Allah Mabuwayi ne, kuma mai uƙuba ne.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci hukuncin farautar dabbar tudu, sai kuma ya bayyana cewa farautar naman ruwa da abincin cikinsa, wanda kogi ya yi ambaliyarsa cewa halal ne ga waɗanda suke sanye da Harami, kuma halal ne ga matafiya. Farautar naman ruwa shi ne duk abin da aka kama da rai, abincin ruwa kuwa shi ne abin da ya mutu a cikin kogi wanda ya furzo shi waje, ko ya taso saman ruwa. Allah ya halatta waɗannan ne ga bayinsa lokacin zaman gida ko cikin halin tafiyar. Don haka a ko'ina suke su kiyaye dokokin Allah, wanda za a tattara su a gabansa, makomarsu gaba ɗaya kuma zuwa gare shi take, kuma zai yi musu hisabi bisa ga ayyukansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman sha'anin Ka'aba ɗakin Allah. Ubangiji ya sanya ta ta zama mai amfani ga mazauna garin Makka, a dalilinta kuma Allah ya sanya wannan gari ya zama amintacce.

2. Duk wanda ya amfana da samuwar ɗakin Ka'aba babu kamar Larabawa, saboda ta zamanto sanadiyyar fahimtarsu ga Tauhidi da bin addinin Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Lokacin da Musulunci ya bayyana, sai hajji zuwa ɗakin Ka'aba ya zamanto ɗaya daga cikin manya-manyan ayyukan Musulunci wanda ake kankare zunuban bawa da shi.

3. Girmama sha'anin hadaya da kwaɗaitarwa a kan yin ta.

4. Halaccin yi wa dabbar layya alama don a gane ta a tsakanin sauran dabbobi.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa ambaton azaba tare da ambaton rahama domin bayinsa su fahimci cewa sai da haɗa tsoro da kyakkyawan fata ne ake samun tsira.

6. Annabi (ﷺ) bai zamanto mai tilasta wa mutane su shiga Musulunci ba; shi mai isar da saƙo ne kawai, wanda ya ga dama ya karɓa ya yi imani, wanda ya ga dama kuma ya ƙi karɓa, kowa dai zai gamu da sakamakonsa a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

7. A wurin Allah da kuma mutane masu lafiyayyen hankali, mummunan abu da kyakkyawa ba za su taɓa zama daidai ba. Amma a cikin ayyuka na duniya, mummuna zai iya fin kyakkyawan yawa, kamar yadda yake faruwa a rayuwar mutane ta yau. Yawa kaɗai ba shi ne ma'aunin gane daidai ko rashin daidai a wurin Allah ba.

8. Har koyaushe masu hankali su ne masu fahimtar abubuwa yadda suke. Don haka mumini shi ne mai lafiyayyen hankali a wurin Allah Ta'ala.

Suratul Ma'ida (97-100)

۞جَعَلَ ٱللَّهُ ٱلۡكَعۡبَةَ ٱلۡبَيۡتَ ٱلۡحَرَامَ قِيَٰمٗا لِّلنَّاسِ وَٱلشَّهۡرَ ٱلۡحَرَامَ وَٱلۡهَدۡيَ وَٱلۡقَلَٰٓئِدَۚ ذَٰلِكَ لِتَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَأَنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٌ ٩٧ ٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ وَأَنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٩٨ مَّا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُۗ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا تُبۡدُونَ وَمَا تَكۡتُمُونَ ٩٩ قُل لَّا يَسۡتَوِي ٱلۡخَبِيثُ وَٱلطَّيِّبُ وَلَوۡ أَعۡجَبَكَ كَثۡرَةُ ٱلۡخَبِيثِۚ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ يَٰٓأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ١٠٠

97. Allah Ya sanya Ka'aba ɗaki ne mai alfarma, wuri mai matuƙar amfani ga mutane, haka watanni masu alfarma, da dabbar hadaya da dabbar hadaya mai rataye. Wannan kuwa don ku sani cewa, lalle Allah Ya san abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa, kuma lalle Allah Masanin komai ne.

98. Ku sani lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne, kuma lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

99. Babu abin da yake kan Manzo sai isarwa. Kuma Allah Yana sane da abin da kuke bayyanawa da abin da kuke ɓoyewa.

100. Ka ce: "Mummuna da kyakkyawa ba za su taɓa zama daidai ba, ko da kuwa yawan mummunan ya burge ka." Don haka ku kiyaye dokokin Allah, ya ku ma'abota hankali, don ku sami rabauta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa ya sanya Ka'aba ɗaki mai alfarma, wani wuri mai amfani ga mutane inda suke samun biyan buƙatunsu na addini, kamar hajji da umara da salloli da ɗawafi da kuma sauran amfanin duniya, kamar gudanar da harkar kasuwanci da samun zaman lafiya da kwanciyar hankali da samun sanayya da taimakon juna a tsakanin Musulmi. Hakanan ya sanya wata mai alfarma wanda a cikinsa mutane suna samun aminci da kwanciyar hankali saboda haramta yaƙe-yaƙe a cikinsa. Hakanan da hadaya da dabbobi, kamar raƙuma da shanu da ƙananan dabbobi da waɗanda aka yi musu alamomi na musamman domin nuna keɓance su don bautar Allah. Dukkansu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya su ababen kusantar sa da su ne, kuma mutane suna amfana da su tare da cim ma wasu buƙatunsu ta hanyarsu. Allah ya yi haka ne don mutane su san cewa, yana sane da abin da yake cikin sama da wanda yake ƙasa, don haka shi ne ya fi kowa sanin abin da yake maslaha ga bayinsa a addininsu da rayuwarsu, kuma Allah masanin komai ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da mutane uƙubarsa, ya kuma kwaɗaitar da su ladansa, ya umarce su da su san cewa shi mai tsananin uƙuba ne ga duk wanda ya saɓa masa, kuma mai gafara ne ga wanda ya tuba ya koma gare shi, zai yafe masa laifukansa, kuma shi mai rahama ne ga bayinsa.
Ya ƙara da cewa babu wani abu da ya rataya a wuyan Annabi (ﷺ) sai isar da saƙon da aka aiko shi da shi, kuma bai yi ƙasa a gwiwa ba, sai da ya isar da duk wani saƙo da aka umarce shi da ya isar. Kuma Allah yana sane da abin da bayinsa suke bayyanawa da wanda suke ɓoyewa na ayyukansu, kuma duk zai yi musu sakayya a kansu.
Sai ya umarci Annabinsa da ya faɗa wa mutane cewa, mummuna da kyakkyawa ba za su taɓa zama daidai ba, ko da yawan mummunan yana burge mutum. Don haka, ya yi kira ga masu lafiyayyun hankula kan su kiyaye dokokin Allah domin su sami abin da suke fatan su samu, su kuma kuɓuta daga abin da suke ƙi duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bai dace mumini ya matsa da tambaya a kan abin da ba a umarce shi da aiki da shi ba.

2. Alƙur'ani bai sauka don tabbatar da aƙida ko shari'a ba kawai; ya zo ne don tarbiyyar al'umma da samar da Musulmai nagari waɗanda za su tafiyar da rayuwarsu a kan tsarin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai cike da hikima da tarbiyya da kyakkyawan tsarin zamantakewar ɗan'adam.

3. Bai kamata ga Musulmi ba ya jefa kansa cikin abin da yake halaka ne gare shi yana sane.

4. Kutsa kai cikin fatawa da halattawa da haramtawa ba tare da ilimi ba, rashin hankali ne.

5. Duk wanda zai ƙagi wata shari'a ko wani hukunci sabo ya jingina shi ga Musulunci da gangan, to lalle yana daga cikin masu yi wa Allah ƙarya da shisshigi.

6. Wanda zai kafe a kan maganar malaminsa ko shehinsa da ta saɓa da faɗar Allah da Manzonsa, yana sane, to lalle ya kwaikwayi aiki ne irin na mushrikai waɗanda suka bijire wa gaskiya saboda ta saɓa wa aikin iyayensu.

7. Mutum ya fara da gyara zuciyarsa da kula da kansa, yin haka yana daga cikin imani.

8. Wajabcin yin umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna ga wanda yake da ikon haka. Bayan wannan, to wanda duk ya bijire wa gaskiya ba zai cutar da mabiyanta da komai ba.

9. Duk abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Manzonsa (ﷺ) suka yi shiru a kansa, to ya shiga cikin da’irar abubuwan da aka yi afuwa a kansu.

Suratul Ma’ida (101-105)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَسۡـَٔلُواْ عَنۡ أَشۡيَآءَ إِن تُبۡدَ لَكُمۡ تَسُؤۡكُمۡ وَإِن تَسۡـَٔلُواْ عَنۡهَا حِينَ يُنَزَّلُ ٱلۡقُرۡءَانُ تُبۡدَ لَكُمۡ عَفَا ٱللَّهُ عَنۡهَاۗ وَٱللَّهُ غَفُورٌ حَلِيمٞ ١٠١ قَدۡ سَأَلَهَا قَوۡمٞ مِّن قَبۡلِكُمۡ ثُمَّ أَصۡبَحُواْ بِهَا كَٰفِرِينَ ١٠٢ مَا جَعَلَ ٱللَّهُ مِنۢ بَحِيرَةٖ وَلَا سَآئِبَةٖ وَلَا وَصِيلَةٖ وَلَا حَامٖ وَلَٰكِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يَفۡتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَۖ وَأَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡقِلُونَ ١٠٣ وَإِذَا قِيلَ لَهُمۡ تَعَالَوۡاْ إِلَىٰ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ وَإِلَى ٱلرَّسُولِ قَالُواْ حَسۡبُنَا مَا وَجَدۡنَا عَلَيۡهِ ءَابَآءَنَآۚ أَوَلَوۡ كَانَ ءَابَآؤُهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ شَيۡـٔٗا وَلَا يَهۡتَدُونَ ١٠٤ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ عَلَيۡكُمۡ أَنفُسَكُمۡۖ لَا يَضُرُّكُم مَّن ضَلَّ إِذَا ٱهۡتَدَيۡتُمۡۚ إِلَى ٱللَّهِ مَرۡجِعُكُمۡ جَمِيعٗا فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ١٠٥

101. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku yi tambaya game da waɗansu al’amurra, waɗanda idan aka bayyana muku su za su dame ku, idan kuwa kuka riƙa tambaya game da su yayin da Alƙur’ani yake sauka, za a bayyana muku su; Allah Ya yi rangwame game da su. Kuma Allah Mai gafara ne, Mai haƙuri.
102. Haƙiƙa waɗansu mutane gabaninku sun yi irin wannan tambayar, sannan suka wayi gari suna kafirce mata.

103. Allah bai sanya wata dabba *bahîra* ba ko *sá’iba* ko *wasîla* ko *hám*ba, sai dai waɗanda suka kafirta suna ƙirƙirar ƙarya su jingina wa Allah; kuma yawancinsu ba sa hankalta.

104. Kuma idan aka ce da su: “Ku taho zuwa ga abin da Allah Ya saukar da kuma zuwa ga Manzo,” sai su ce: “Abin da muka sami iyayenmu a kai ya ishe mu.” Yanzu ko da iyayen nasu sun kasance ba su san komai ba, kuma ba sa shiryuwa?

105. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi ta kanku; wanda ya ɓata, ba zai cutar da ku ba idan har ku kun shiryu. Zuwa ga Allah ne makomarku take gaba ɗaya, sannan kuma zai ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa muminai kashedi game da yawan tambaya a kan wasu abubuwa da ba a saukar da hukunci a kansu ba; yin hakan zai jawo Allah ya bayyana musu wani hukuncin da ba zai yi musu daɗi ba. Amma idan sun yi tambayar ne a kan wani abu da Allah ya riga ya saukar musu da hukuncinsa a Alƙur’ani, to babu wata matsala a nan, saboda sun yi tambaya ne a kan gaba, sai Allah ya bayyana musu abin da suke tambaya a kansa. Allah ya yafe musu laifin tambayoyin da suka riƙa yi a baya. Allah mai gafara ne, mai haƙuri da bayinsa.

An karɓo daga Anas (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ce: “Wata rana Annabi (ﷺ) ya sami wani labari game da sahabbansa, sai ya je ya yi musu huɗuba. Ya ce: “An nuna mini Aljanna da wutar Jahannama, ban taɓa ganin wani alheri da wani sharri irin na yau ba. Da a ce kun san abin da na sani, da kun yi dariya ‘yar kaɗan, kun yi kuka mai yawa.” Anas ya ce: “Sahabban Manzon Allah (ﷺ) ba su taɓa shiga wani tsanani irin wannan rana ba, sai suka lulluɓe kawunansu suna kuka. Sai Umar ya miƙe tsaye ya ce: “Mun yarda da Allah ne Ubangiji, Musulunci ne addini, kuma Muhammadu Annabi ne.” Sai kuma wani mutum shi ma ya miƙe tsaye ya ce: “Wane ne babana?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: “Wane shi ne babanka.” Sai wannan ayar ta sauka. [Bukhari #7295, da Muslim #2359].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ya ku mutane, Allah ya wajabta muku aikin Hajji, don haka ku je ku yi hajji.” Sai wani mutum ya yi tambaya cewa: “A kowace shekara ne ya Manzon Allah?” Sai Manzon Allah ya yi shiru. Ya sake tambayar sa har sau uku, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: “Da na ce na’am, to da ta zama wajibi (wato hajji duk shekara), da kuma ba za ku iya ba.” Sannan ya ce: “Ku ƙyale ni matuƙar na ƙyale ku, domin waɗanda suka gabace ku sun halaka ne a dalilin yawan tambayoyinsu da sassaɓa wa annabawansu, don haka idan na umarce ku da wani abu, to ku aikata shi gwargwadon ikonku; idan kuma na hana ku abu, to ku nisance shi.” [Muslim #1337].

An karɓo daga Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Musulmin da ya fi kowa girman laifi shi ne wanda ya yi tambaya a kan wani abu da ba a haramta shi ba, sai aka haramta shi saboda tambayarsa.” [Bukhari #289, da Muslim #2358].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa wasu mutane da suka gabace su sun riƙa yin irin waɗannan tambayoyin da aka hana su, bayan an amsa musu tambayoyinsu sai suka kafirce wa amsoshin da aka ba su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin wasu ayyukan na kafirci da Larabawa suke yi kafin zuwan Musulunci. Sun riƙa ware wasu dabbobi suna haramta wa kawunansu cin namansu ko hawansu; daga cikinsu akwai:
• ***Bahira***, Ita ce taguwar da suka tsaga kunnuwanta saboda ta haihu har sau biyar, to namanta ya zama haramun ga mata suci, kuma nononta ya zama na gumaka, babu mai tatsar ta.
• ***Sa’iba***, ita ce taguwar da mai ita yake bar wa gumaka ita, yayin da ya yi bakance da cewa, idan ya dawo daga tafiyarsa lafiya, ko idan ya yi rashin lafiya ya ce idan ya warke daga rashin lafiyarsa, to zai ware wa gumaka wata taguwa wadda ba za a yanka ta a ci ba, kuma ba za a ɗora mata kaya ba; za a bar ta ta yi kiwo a duk inda take so, ta sha ruwan da take so, ba mai hana ta.
• ***Wasila***, ita ce dabbar da ta yi haihuwa bakwai, idan na bakwan ya zama namiji ne, to sai a yanka shi maza da mata su ci namansa, idan mace ce, sai su ƙyale ta, idan kuwa tagwaye ta Haifa; mace da namiji, sai su ce, macen ta ceci ɗan’uwanta, sai a ƙyale su duka biyun, namansu ya haramta ga mata, nonon tamacen ma ya haramta ga mata, sai idan sun mutu, to maza da mata suna iya cin namansu.
• ***Hamu***, shi ne namijin garke wanda aka haifi ‘ya’ya goma daga tsatsonsa, to shi ma suna cewa ya ‘yanta bayansa, sai a bar shi ga gumaka, ba a ɗora masa kaya, ba a hawansa.Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, duk waɗannan hukunce-hukunce nasu ba daga Allah suke ba; ƙarya ce suka ƙirƙira kuma suka riƙa jingina wa Allah, kuma da dama daga cikinsu ba su da hankali. Idan aka ce musu, su zo ga Littafin Allah da Manzonsa (ﷺ) don ya bayyana musu addinin Allah da shari’arsa, sai kawai su amsa da cewa, abin da suka sami iyayensu a kai ya ishe su. To ta yaya za su riƙa faɗar irin wannan zance, duk da cewa iyayensu jahilai ne, ba su san komai ba, ɓatattu ne, ba su san shiriya ba?Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa, idan har su suka tsaya a kan abin da Allah ya umarce su da shi, to duk wanda ya zaɓi ya kama hanyar ɓata ba zai cuce su da komai ba; makomarsu gaba ɗaya zuwa ga Allah ne, kuma zai ba su labarin abin da suka kasance suna aikatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman sha’anin wasiyya da muhimmancinta; don nuna muhimmancinta ne ma Allah ya yi umarni da ita har a cikin halin tafiya lokacin da aka yi wa mutum rangwamen wasu abubuwa a cikinta.

2. Ana la’akari da wasiyya ko da mutum yana cikin halin mutuwa, matuƙar hankalinsa bai rabu da shi ba.

3. Yana da kyau samun masu shaida a kan wasiyya. Ana so a sami maza biyu Musulmi adalai, ko kuma namiji ɗaya da mata biyu idan an rasa mazaje zalla, kamar yadda aya ta 282 ta *Suratul Bakara* ta nuna.

4. Idan an rasa adalai, to sai a shaidar da fasiƙi, musamman idan mai amana ne.5. Halaccin kafa shaida da kafiri yayin da aka rasa Musulmi, domin rashin yin haka na iya jawo salwantar wasu haƙƙoƙi.

6. Halaccin Musulmi ya yi tafiya da kafiri, matuƙar babu wata cutuwa a ciki.

Suratul Ma'ida (106-108)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ شَهَـٰدَةُ بَيۡنِكُمۡ إِذَا حَضَرَ أَحَدَكُمُ ٱلۡمَوۡتُ حِينَ ٱلۡوَصِيَّةِ ٱثۡنَانِ ذَوَا عَدۡلٖ مِّنكُمۡ أَوۡ ءَاخَرَانِ مِنۡ غَيۡرِكُمۡ إِنۡ أَنتُمۡ ضَرَبۡتُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَأَصَـٰبَتۡكُم مُّصِيبَةُ ٱلۡمَوۡتِۚ تَحۡبِسُونَهُمَا مِنۢ بَعۡدِ ٱلصَّلَوٰةِ فَيُقۡسِمَانِ بِٱللَّهِ إِنِ ٱرۡتَبۡتُمۡ لَا نَشۡتَرِي بِهِۦ ثَمَنٗا وَلَوۡ كَانَ ذَا قُرۡبَىٰ وَلَا نَكۡتُمُ شَهَـٰدَةَ ٱللَّهِ إِنَّآ إِذٗا لَّمِنَ ٱلۡأٓثِمِينَ ١٠٦ فَإِنۡ عُثِرَ عَلَىٰٓ أَنَّهُمَا ٱسۡتَحَقَّآ إِثۡمٗا فَاخَرَانِ يَقُومَانِ مَقَامَهُمَا مِنَ ٱلَّذِينَ ٱسۡتَحَقَّ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَوۡلَيَـٰنِ فَيُقۡسِمَانِ بِٱللَّهِ لَشَهَـٰدَتُنَآ أَحَقُّ مِن شَهَـٰدَتِهِمَا وَمَا ٱعۡتَدَيۡنَآ إِنَّآ إِذٗا لَّمِنَ ٱلظَّـٰلِمِينَ ١٠٧ ذَٰلِكَ أَدۡنَىٰٓ أَن يَأۡتُواْ بِٱلشَّهَـٰدَةِ عَلَىٰ وَجۡهِهَآ أَوۡ يَخَافُوٓاْ أَن تُرَدَّ أَيۡمَـٰنُۢ بَعۡدَ أَيۡمَـٰنِهِمۡۗ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَٱسۡمَعُواْۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡفَـٰسِقِينَ ١٠٨

106. Ya ku waɗanda suka yi imani, shaidar da take tsakaninku idan alamun mutuwa suka zo wa ɗaya daga cikinku, yayin da ya so ya yi wasiyya, shi ne a samu mutum biyu masu adalci daga cikinku ko kuma waɗansu biyu daga wasunku (kafirai), yayin da kuka yi tafiya a bayan ƙasa, sai musibar mutuwa ta same ku. Za ku tsayar da su (shaidun) biyun ne bayan an kammala salla, sai su rantse da Allah- idan har kun yi shakka game da su-: "Wallahi, ba za mu musanya shi da wani farashi ba, ko da kuwa ya zamo ma'abocin kusanci ne, kuma ba za mu ɓoye shaidar Allah ba, lalle kuwa idan har muka yi haka, tabbas muna cikin masu laifi."

107. Amma idan an gano cewa su biyun sun yi laifi, sai a nemi mutum biyu su tsaya su yi shaida a madadin waɗancan daga cikin waɗanda suka cancanta su ci gadonsa, sai su rantse da Allah: "Wallahi, shaidarmu ta fi shaidarsu, kuma wallahi ba mu ƙetare iyaka ba, lalle kuwa idan mun yi haka, tabbas da mun zama cikin azzalumai."

108. Yin haka shi ne ya fi kusa da su kawo shaida kamar yadda take, ko su ji tsoron a mayar da wannan shaidar bayan rantsuwarsu. Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku saurari (umarninsa), kuma Allah ba Ya shiryar da mutanen da suke fasiƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana magana da muminai ne yayin da ɗayansu mutuwa ta zo masa, ya rubuta wasiyyarsa ta ƙarshe, to lalle a sami muminai biyu adalai su yi shaida a kai; idan kuwa a cikin halin tafiya ne mutuwar ta zo masa, kuma bai sami Musulmai masu yi masa shaidar ba, to sai ya sanya waɗanda ba Musulmi ba su zama shaida. To Musulmi za su tsayar da waɗannan shaidu waɗanda ba Musulmi ba, bayan sallar la'asar. Idan ana da shakka a kan shaidarsu ko aka ga wasu alamu da za su hana a nutsu da su, sai a nemi su yi rantsuwa da Allah cewa babu wani abu na duniya da suke nema da zai sa har su yi ƙarya, kuma ba za su yi wa wani ƙarya ba ko da ɗan'uwansu ne makusanci, ba kuma za su ɓoye wata shaida da suke tare da ita ba, kuma in har sun aikata haka, to sun tabbata daga cikin masu laifi.
To idan daga baya an gano cewa sun faɗi ƙarya a shaidarsu ko sun canza wasiyyar mamacin ko sun ɓoye wani abu, to sun zama masu laifi, sai a sami wasu mutanen biyu daga cikin magadan mamaci, su tsaya a madadin waɗancan mutane biyu na farko, su rantse da Allah cewa shaidarsu ta fi shaidar waɗancan da ba Musulmi ba inganci, kuma ba su ƙetare iyaka ba wajen bayar da tasu shaidar ko zargin shaidar waɗancan da ba Musulmi ba, domin idan har sun yi musu ƙarya, to su ma sun zama azzalumai.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, neman shaidun nan biyu su rantse yayin da ake da shakka a kansu, shi ne zai sa a samu kyakkyawar shaida mai inganci da babu ƙarya a cikinta kuma babu ha'inci. Sai kuma Allah ya umarci bayinsa da su ji tsoron sa ta hanyar kiyaye dokokinsa, kuma su saurari abin da ake umartar su da shi, su yi aiki da shi. Ya kuma nuna cewa ba ya datar da mutanen da suke fasiƙai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Wani mutum ɗan ƙabilar Banu Sahmin sun yi tafiya tare da Tamimuddari (lokacin bai musulunta ba) tare da Adiyyu ɗan Badda'u, sai wannan mutumin ya rasu a wani gari wanda babu Musulmi a cikinsa. Lokacin da aka kawo kayansa na gado, sai magadansa ba su ga wani ƙoƙon azurfa wanda aka yi masa kwalliya da zinari a cikin kayan ba. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya nemi Tamimuddari da Adiyyu da su rantse. Sai suka rantse. Daga baya aka gano wannan ƙoƙon a wurin wasu mutane a Makka, da aka tambaye su, ko ina suka same shi? Sai suka ce, sayensa suka yi a hannun Tamimuddari da Adiyyu. Sai mutum biyu cikin magadan wannan mamacin suka tashi tsaye suka yi rantsuwa cewa shaidarsu ta fi shaidar su Tamimuddari, kuma wannan ƙoƙo na ɗan'uwansu ne da ya mutu." Abdullahi ɗan Abbas ya ce: "A kansu ne wannan aya ta 106 ta sauka." [Dubi, Bukhari #2780].
An karɓo daga Amiru Assha'abi ya ce: Wani mutum mutuwa ta same shi a wani gari da ake kira *Daƙuƙa'u*, bai sami Musulmi da zai kafa shaida a kan wasiyyarsa ba, sai ya shaidar da wasu mutane biyu daga cikin Ma'abota Littafi. Da suka kawo kayan gadon da ya bari wurin Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya kara masa yarda), sai suka ba shi labarin abin da ya faru. Sai Abu Musa Al-Ash'ari ya ce: "Wannan al'amari tun sa'adda ya faru a zamanin Manzon Allah (ﷺ) bai sake faruwa ba sai yanzu." Sai ya saka su suka yi rantsuwa da Allah bayan sallar La'asar cewa, ba su ci amana ba kuma ba su faɗi ƙarya ba kuma ba su canza wasiyya ba; wannan kayan da suka kawo su ne abin da ya mutu ya bari. Sai Abu Musa ya zartar da shaidarsu. [Abu Dawud #3605].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman matsayin manzannin Allah.

2. Tunatar da bawa wannan rana da za a tambayi manzanni game da irin amsar da aka ba su a duniya.

3. Tunatar da ɗan'adam ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa da wajabcin godiya a kansu, musamman ni'imar ilimi da Allah zai yi wa bawansa, wajibi ne a gare shi ya gode masa ta hanyar aiki da wannan ilimin da karantar da shi da kira zuwa ga Allah da haƙuri a kan hakan.

4. Bayani a kan kariya da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi wa bayinsa muminai daga sharrin maƙiyansu. Wannan ni'ima ce daga Allah, wajibi ne a kansu su yi masa godiya.

5. Wajibi ne a kan annabawa su ma su gode wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kamar yadda yake wajibi a kan sauran mutane.

6. Falalar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da bayanin irin ni'imomi masu yawa da Allah ya yi masa, wanda hakan ya jawo masa yawan mahassada a cikin Banu Isra'ila. Don haka duk wanda Allah ya yi wa ni'ima dole ne ya gamu da mahassada.

7. Falalar mala'ika Jibrilu, wanda da shi ne Allah yake ƙarfafar annabawa da manzanni.

8. Duk abin da ya gudana a hannun Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) na mu'ujizoji ya gudana ne da izinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Don haka babu wani mutum, duk matsayinsa, da zai cim ma muradinsa ba tare da izinin Allah ba.

Suratul Ma'ida (109-110)

*يَوۡمَ يَجۡمَعُ ٱللَّهُ ٱلرُّسُلَ فَيَقُولُ مَاذَآ أُجِبۡتُمۡۖ قَالُواْ لَا عِلۡمَ لَنَآۖ إِنَّكَ أَنتَ عَلَّٰمُ ٱلۡغُيُوبِ ١٠٩ إِذۡ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبۡنَ مَرۡيَمَ ٱذۡكُرۡ نِعۡمَتِي عَلَيۡكَ وَعَلَىٰ وَٰلِدَتِكَ إِذۡ أَيَّدتُّكَ بِرُوحِ ٱلۡقُدُسِ تُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِي ٱلۡمَهۡدِ وَكَهۡلٗاۖ وَإِذۡ عَلَّمۡتُكَ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَٱلتَّوۡرَىٰةَ وَٱلۡإِنجِيلَۖ وَإِذۡ تَخۡلُقُ مِنَ ٱلطِّينِ كَهَيۡـَٔةِ ٱلطَّيۡرِ بِإِذۡنِي فَتَنفُخُ فِيهَا فَتَكُونُ طَيۡرَۢا بِإِذۡنِيۖ وَتُبۡرِئُ ٱلۡأَكۡمَهَ وَٱلۡأَبۡرَصَ بِإِذۡنِيۖ وَإِذۡ تُخۡرِجُ ٱلۡمَوۡتَىٰ بِإِذۡنِيۖ وَإِذۡ كَفَفۡتُ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ عَنكَ إِذۡ جِئۡتَهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡهُمۡ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ مُّبِينٞ ١١٠

109. (Ka tuna) ranar da Allah zai tara manzanni, sannan Ya ce: "Da me aka ba ku amsa?" sai su ce: "Ba mu da wata masaniya; lalle Kai ne kaɗai Masanin abubuwan da suke ɓoye."

110. (Ka tuna) lokacin da Allah zai ce: "Ya kai Isa ɗan Maryamu, ka tuna ni'imata da Na yi maka kai da mahaifiyarka, yayin da Na ƙarfafe ka da Ruhi mai tsarki, kana yi wa mutane magana lokacin kana cikin zanin goyo, da kuma lokacin da kake dattijo, kuma ka tuna lokacin da Na koyar da kai rubutu da hikima da Attaura da Linjila. Kuma ka tuna lokacin da kake ƙirƙirar (wani abu) kamar tsuntsu da taɓo da izinina, sai ka yi busa a cikinsa, sai ya zamo tsuntsu da izinina; kuma kake warkar da wanda aka haifa da makanta da mai albaras da izinina; kuma ka tuna lokacin da kake fito da matattu (daga cikin ƙaburburansu) da izinina; kuma ka tuna lokacin da Na kare ka (daga cutar) Bani Isra'ila yayin da ka zo musu da hujjoji bayyanannu, sai waɗanda suka kafirta daga cikinsu suka ce: "Ai wannan ba komai ba ne face sihiri mabayyani."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wasu al'amura da za su faru a ranar Alƙiyama lokacin da zai tattara manzanni wuri guda ya tambaye su irin amsar da suka samu daga al'ummominsu bayan sun isar musu da kiran Allah. Sai manzanni su ba da amsa da cewa ba su da wani ilimi dangane da haka, Allah shi ne masanin gaibu.
Sai kuma ya bayyana abin da ya faɗa wa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa: "Ya kai Isa ɗan Maryam, ka tuna ni'imar da na yi maka kai da mahaifiyarka, lokacin da na taimake ka, na ƙarfafe ka da Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kana magana da mutane tun kana ɗan ƙaraminka da kuma lokacin girmanka. Kuma ka tuna lokacin da na koyar da kai rubutu; na ba ka fahimtar sirrukan shari'a, na koyar da kai littafin Attaura da littafin Linjila. Kuma ka tuna lokacin da kake mulmula wani abu mai kama da tsuntsu da taɓo da izinina, sai kuma ka yi busa a cikinsa, sai ya zama tsuntsu mai rai da izinina. Kuma ka riƙa warkar da wanda aka haifa makaho da mai cutar albaras da izinina; kuma kake fito da matattu da ransu daga ƙaburburansu da izinina. Kuma na kare ka daga sharrin Banu Isra'ila lokacin da suka so ƙashe ka yayin da ka zo musu da hujjoji bayyanannu, sai kafiran cikinsu suka ce maka, abin da ka zo da shi sihiri ne a bayyane."

Daga waɗannan ayoyin za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) baiwar mabiya masu taimakon sa wajen isar da saƙon da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko shi da shi.

2. Duk wani mai kira ga Allah yana buƙatar wasu amintattun mutane kusa da shi don taimaka masa a kan harkar da'awarsa zuwa ga Allah.

3. Imani shi ne gaba da Musulunci, shi ya sa Hawariyyawa suka fara gabatar da shi a kan Musuluncinsu, domin shi ne yake da alaƙa da zuciya kai-tsaye.

4. Imanin bawa yana ƙaruwa yayin da ya ga wata aya ta Ubangiji da idonsa, ko ma ya ji ta da wata gaɓa ta jikinsa, yakan sami ilimi na yaƙini ta hakan.

5. Imani yana ƙaruwa yana kuma raguwa.

6. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) mai buƙatuwa ne zuwa ga Allah a komai; ba ya iya amsa buƙatar wani sai da taimakon Allah da izininsa.

7. Almajiran Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) na farko sun fahimci shi ba Allah ne ba; shi bawan Allah ne, Manzonsa, don haka suna neman addu'arsa ne, ba shi suke roƙo ya biya musu buƙatunsu da kansa ba.
8. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nemi a saukar musu da kaɓakin abinci daga sama don cim ma maslahohi guda biyu: Ta farko, maslahar addini, wato ta zama mu'ujiza, wato shaida a kan gaskiyar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi); ta biyu, ta zama arzikin da za su ci daga gare shi.

9. Bayanin haɗarin kafirci bayan hujja ta bayyana. Kuma wanda ya kafirce bayan kafuwar hujja a kansa, azabarsa ta fi tsanani fiye da wanda bai ga irin wannan hujjar ba.

Suratul Ma'ida (111-115)

وَإِذۡ أَوۡحَيۡتُ إِلَى ٱلۡحَوَارِيِّـۧنَ أَنۡ ءَامِنُواْ بِي وَبِرَسُولِي قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَٱشۡهَدۡ بِأَنَّنَا مُسۡلِمُونَ ١١١ إِذۡ قَالَ ٱلۡحَوَارِيُّونَ يَٰعِيسَى ٱبۡنَ مَرۡيَمَ هَلۡ يَسۡتَطِيعُ رَبُّكَ أَن يُنَزِّلَ عَلَيۡنَا مَآئِدَةٗ مِّنَ ٱلسَّمَآءِۖ قَالَ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١١٢ قَالُواْ نُرِيدُ أَن نَّأۡكُلَ مِنۡهَا وَتَطۡمَئِنَّ قُلُوبُنَا وَنَعۡلَمَ أَن قَدۡ صَدَقۡتَنَا وَنَكُونَ عَلَيۡهَا مِنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ١١٣ قَالَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ ٱللَّهُمَّ رَبَّنَآ أَنزِلۡ عَلَيۡنَا مَآئِدَةٗ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ تَكُونُ لَنَا عِيدٗا لِّأَوَّلِنَا وَءَاخِرِنَا وَءَايَةٗ مِّنكَۖ وَٱرۡزُقۡنَا وَأَنتَ خَيۡرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ١١٤ قَالَ ٱللَّهُ إِنِّي مُنَزِّلُهَا عَلَيۡكُمۡۖ فَمَن يَكۡفُرۡ بَعۡدُ مِنكُمۡ فَإِنِّيٓ أُعَذِّبُهُۥ عَذَابٗا لَّآ أُعَذِّبُهُۥٓ أَحَدٗا مِّنَ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١١٥

111. Kuma ka tuna lokacin da Na yi wahayi zuwa ga Hawariyyawa: "Ku yi imani da Ni da Manzona," sai suka ce: "Mun yi imani, kuma Ka shaida cewa, mu Musulmai ne."

112. Lokacin da Hawariyyawa suka ce: "Ya Isa ɗan Maryamu, shin Ubangijinka Yana iya saukar mana da kaɓaki daga sama?" Ya ce: "Ku kiyayi Allah, idan har kun kasance muminai."

113. Suka ce: "Mu muna nufin mu ci daga gare shi, kuma zukatanmu su sami nutsuwa, sannan mu haƙiƙance cewa, lalle ka faɗa mana gaskiya, kuma mu zamo masu ba da shaida a kansa."

114. Isa ɗan Maryamu ya ce: "Ya Allah Ubangijinmu, Ka saukar mana da kaɓaki daga sama, wanda zai zame mana wani Idi, ga na farkonmu da na ƙarshenmu, kuma ya zamo wata aya daga gare Ka; kuma Ka arzuta mu, lalle Kai ne Fiyayyen masu arzutawa."

115. Allah Ya ce: “Lalle Ni Mai saukar muku da shi (kaɓakin) ne; amma duk wanda ya kafirta daga baya cikinku, to lalle Ni zan yi masa wata irin azaba wadda ba zan taɓa azabtar da wani daga cikin halittu irinta ba.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da Annabinsa Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mabiyan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi da yadda ya kimsa wa zaɓaɓɓun cikinsu, su ne Hawariyyawa, da su yi imani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Manzonsa Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai suka shelanta imaninsu, suka neme shi ya zamo shaidarsu a kan su Musulmi ne masu miƙa wuya.
Sannan ya tunatar da shi lokacin da Hawariyyawa suka tambaye shi cewa, idan ya roƙi Ubangijinsa ya saukar musu da kaɓakin abinci daga sama, zai iya yi masa haka? Sai Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ja kunnensu da cewa, lalle su ji tsoron Allah, su daina kawo irin waɗannan buƙatu idan har da gaske su muminai ne. Sai suka amsa masa da cewa, su suna so ne su ci daga wannan kaɓaki domin zukatansu su ƙara samun nutsuwa, su ƙara fahimtar cewa Annabi Isa mai gaskiya ne a kan abin da ya zo musu da shi, kuma su zama shaida a kan wannan mu’ujizar da za su gani da idanunsu cewa lalle daga Allah take, kuma su isar da labarinta ga sauran mutane. To sai Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi addu’a, ya roƙi Allah a kan ya saukar musu da wani kaɓaki daga sama da zai zama musu idi gare su da waɗanda za su zo daga baya, kuma ya zama wani dalili wanda yake nuna Ɗayantakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), yake kuma tabbatar da gaskiyar abin da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo da shi, kuma Allah ya arzuta su domin shi ne Fiyayyen masu arzutawa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa masa da cewa, zai saukar musu da wannan kaɓaki da suka nema, amma kuma duk wanda ya kafirce masa bayan ya saukar da shi, to fa zai gamu da wata matsananciyar azaba wadda wani a cikin halittun Allah bai taɓa shan irinta ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifiyarsa Maryamu ba alloli ne ba.

2. Wanda duk ya bauta wa Allah tare da bautar wani, to bai bauta wa Allah ba.

3. Duk wanda ya bauta wa wani Annabi ko wani salihin bawa ba Allah ba, to ranar alƙiyama wannan annabi ko wannan salihin bawa zai barranta daga gare shi.

4. Sanin gaibi siffa ce ta Allah shi kaɗai, hatta annabawa ma ba su san gaibu ba sai abin da Allah ya sanar da su.

5. Duk annabawa sun zo ne da umarnin a bauta wa Allah shi kaɗai. Babu ɗaya daga cikinsu da ya yi kira zuwa ga bautarsa ba Allah ba.

6. Annabawa suna sanin abin da al’ummominsu suke ciki ne lokacin da suke raye a tsakaninsu, amma bayan rasuwarsu ba sa sanin komai sai abin da Allah ya sanar da su.

7. Tausayin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ga al’ummarsa. Annabi Muhammadu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana tausayin wannan al’ummar tasa fiye da yadda sauran annabawa suka tausaya wa al’ummominsu.

8. Amfanin gaskiya a ranar alƙiyama. Babu abin da zai kuɓutar da bawa a ranar sai gaskiya.

9. Riba ta haƙiƙa ita ce ribar ranar lahira.

Suratul Ma’ida (116-120)

وَإِذْ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ءَأَنتَ قُلْتَ لِلنَّاسِ ٱتَّخِذُونِي وَأُمِّيَ إِلَٰهَيْنِ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۖ قَالَ سُبْحَٰنَكَ مَا يَكُونُ لِيٓ أَنْ أَقُولَ مَا لَيْسَ لِي بِحَقٍّ ۚ إِن كُنتُ قُلْتُهُۥ فَقَدْ عَلِمْتَهُۥ ۚ تَعْلَمُ مَا فِي نَفْسِي وَلَآ أَعْلَمُ مَا فِي نَفْسِكَ ۚ إِنَّكَ أَنتَ عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ﴿١١٦﴾ مَا قُلْتُ لَهُمْ إِلَّا مَآ أَمَرْتَنِي بِهِۦٓ أَنِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبَّكُمْ ۚ وَكُنتُ عَلَيْهِمْ شَهِيدًا مَّا دُمْتُ فِيهِمْ ۖ فَلَمَّا تَوَفَّيْتَنِي كُنتَ أَنتَ ٱلرَّقِيبَ عَلَيْهِمْ ۚ وَأَنتَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ شَهِيدٌ ﴿١١٧﴾ إِن تُعَذِّبْهُمْ فَإِنَّهُمْ عِبَادُكَ ۖ وَإِن تَغْفِرْ لَهُمْ فَإِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١١٨﴾ قَالَ ٱللَّهُ هَٰذَا يَوْمُ يَنفَعُ ٱلصَّٰدِقِينَ صِدْقُهُمْ ۚ لَهُمْ جَنَّٰتٌ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ ۚ ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿١١٩﴾ لِلَّهِ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا فِيهِنَّ ۚ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ﴿١٢٠﴾

116. Kuma (ka tuna) lokacin da Allah zai ce: “Ya kai Isa ɗan Maryamu, shin kai ne ka ce da mutane: ‘Ku riƙe ni, ni da mahaifiyata a matsayin alloli biyu ban da Allah?’” Sai ya ce: “Tsarki ya tabbata gare Ka, bai dace ba a gare ni in faɗi wani abu wanda ba ni da haƙƙin (faɗar sa). Idan har na faɗe shi, to haƙiƙa Ka riga Ka sani, Ka san abin da yake cikin raina, amma ni ban san abin da yake ranka ba. Lalle Kai ne Masanin abubuwan da suke ɓoye.

117. “Ban faɗa musu komai ba sai abin da Ka umarce ni da shi, cewa: ‘Ku bauta wa Allah Ubangijina, kuma Ubangijinku.’ Kuma na kasance mai sa ido a kansu lokacin da nake cikinsu. Amma yayin da Ka karɓi rayuwata, Ka zama Kai ne Mai kula da su. Kuma lalle Kai Mai kula ne a kan komai.

118. “Idan har Ka azabtar da su, haƙiƙa su bayinka ne; idan kuwa Ka yafe musu, to lalle Kai Mabuwayi ne, Mai hikima.”

119. Allah zai ce: “Wannan ita ce rana wadda gaskiya za ta amfani masu ita. Suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su dawwama a cikinsu har abada. Allah Ya yarda da su, su kuma sun yarda da Shi. Wannan shi ne rabo mai girma.”

120. Mulkin sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu na Allah ne. Kuma Shi Mai iko ne a kan komai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana abin da zai faru tsakaninsa da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a gaban Nasara mabiya addininsa, lokacin da Allah zai tambaye shi cewa, shi ne da mahaifiyarsa suka nemi mutane su riƙa bauta musu ba (bautar) Allah ba? Nan take Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zai ba da amsa da fara tsarkake Ubangijinsa daga duk abin da bai dace ba shi ba, cewa ba zai taɓa yiwuwa a gare shi ba ya faɗi abin da ba haƙƙinsa ba; idan kuwa har ya faɗa, to ai Allah ya sani, domin babu abin da yake ɓuya a gare shi, ya san abin da yake ɓoyewa a ransa, amma shi bai san abin da yake a ransa ba, shi ne masanin duk wani abu da yake ɓoye. Ya tabbatar wa Ubangiji cewa, ba abin da ya faɗa musu, face su bauta masa, domin shi ne Ubangijinsa, kuma Ubangijinsu. Kuma lokacin da yake tare da su yana ganin duk ayyukansu; amma yayin da Allah ya karɓe shi ta hanyar ɗaukarsa zuwa sama, shi kaɗai ya san abin da suke ciki, kuma shi ne mai shaida a kan komai. Idan Allah ya ga dama yana iya azabtar da su domin su bayinsa ne; idan kuma ya gafarta musu, to da ma shi mabuwayi ne, mai hikima cikin ayyukansa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Annabi Muhammadu (ﷺ) ya karanta faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) game da faɗar Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a

gare shi) cewa: “Ya Ubangijina, lalle su (gumaka) sun ɓatar da mutane da yawa, don haka wanda ya bi ni, to shi nawa ne, wanda kuwa ya saɓa mini, to kai mai yawan gafara ne, mai yawan jin ƙai.” Sai kuma ya karanta ayar da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake cewa: “Idan kuwa ka yi musu azaba, to lalle su bayinka ne, idan kuwa ka yi musu gafara, to lalle kai ne mabuwayi mai hikima.” Sai Annabi Muhammadu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ɗaga hannuwansa sama ya ce: “Ya Allah, al’ummata, al’ummata!” Sai ya fashe da kuka. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce da Jibrilu: “Ya Jibrilu, ka je wurin Muhammadu (Ubangijinka ya fi sanin halin da yake ciki), ka tambaye shi, me ya sa ka kuka?” Jibrilu ya zo ya tambaye shi. Sai Annabi (ﷺ) ya faɗa wa Jibrilu abin da Allah ya faɗa (a waɗannan ayoyi biyu). Sai Allah ya ce: “Ya Jibrilu, je ka wajen Muhammadu ka faɗa masa cewa, mu za mu yi maka abin da zai yardar da kai game da al’ummarka, ba za mu ɓata maka rai ba.” [Muslim #202].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa wa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa, wannan rana wadda ita ce ranar alƙiyama, ita ce ranar da gaskiyar masu gaskiya za ta amfane su, suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, masu zama ne a cikinsu har abada, Allah ya yarda da su, su ma sun yarda da shi. Wannan shi ne babban rabo.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi kaɗai yake da mulkin sammai da ƙassai da abin da yake cikinsu, kuma shi mai iko ne a kan komai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yabon kansa tare da cikakkiyar godiya ga kansa lokacin da yake ambatar manya-manyan al’amura masu nuna kamalarsa da cikar Kudurarsa da yalwar rahamarsa, kamar halittar sama da ƙasa, waɗanda suke nuna shi ya cancanci a bauta masa shi kaɗai.

2. Tabbatar da wasu daga cikin ginshiƙan Tauhidi, da tashi bayan mutuwa, domin wanda ya iya halittar ɗan’adam daga taɓo, to zai iya dawo masa da ransa bayan mutuwarsa koda kuwa ya zama rududdugaggun ƙasusuwa.

3. An taƙaita ambaton halittun Allah guda huɗu, watau sammai da ƙasa da duffai da haske, domin nuna lalacewar aƙidun mushirikan Larabawa da Sabi'awa da Majusawa da Nasara, waɗanda dukkansu sun tabbatar da samuwar wasu alloli a bayan ƙasa bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Sabi’awa suna bauta wa taurari, Nasara suna bautar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifiyarsa Maryamu, Majusawa mabiya aƙidar Manawiyya sun ce Allah biyu ne, akwai na haske, shi ne allan alheri, akwai na duhu, shi ne allan sharri. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi ne ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu, kuma shi ya halicci duhu da haske.

4. Yarda da cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san sirrin mutum da abin da yake bayyanawa na ayyukansa, zai ƙara masa tsoron sa, ya sa shi ya guji saɓa masa, ya yi ƙoƙarin aikata abin da ya wajabta masa da aikata duk wani abu da zai kusantar da shi gare shi.



6-Suratul An’am

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna ‘*Suratul An’am*’. Abin da ake nufi da wannan kalma *‘Al-An’am’*; shi ne dabbobin ni’ima. An sa mata wannan suna ne saboda an yi ta maimaita ambatonsu a cikinta.

An karƀo daga Sa’idu ɗan Jubair, daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Idan kana son ka gane jahilcin Labarawa (a zamanin jahiliyya) to ka karanta ayoyin *‘Suratul An’am’* na bayan aya ta ɗari da talatin, (wato daga aya ta 140) tun daga faɗar Allah: “Haƙiƙa waɗannan da suka kashe ‘ya’yansu don wauta, ba tare da ilimi ba sun taɓe….” har zuwa faɗarsa: “Haƙiƙa sun ɓata, kuma ba su kasance shiryayyu ba.” [Bukhari #3524].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce ta hamsin da biyar (55) a jerin saukar surori, ta sauka bayan *‘Suratul Hijr’* gabanin *‘Suratus Saffat’*

.4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Makka da Madina ayoyinta ɗari da sittin da bakwai ne (167). Amma a lissafin mutanen Kufa adadinsu ɗari da sittin da biyar (165), a wurin mutanen Sham da Basra kuwa adadinsu ɗari da sittin da huɗu ne (164).

5. Babban Jigonta:
• Sanar da mutane Ubangijinsu da kiran su zuwa ga bautarsa shi kaɗai ba tare da abokin taryaya ba da kafa dalilai a kan Kaɗaitakarsa da gaskiyar Manzonsa da ranar lahira.
• Kafa hujjoji a kan mushirikai da sauran waɗanda suke ƙaryata tashi bayan mutuwa da rushe ruɗaninsu.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Bayanin cewa Babu wanda ya cancnaci dukkan yabo sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da rushe tasirin duk wani gunki ko aljani, domin Allah shi kaɗai ne ya halicci duniya, ya halicci ɗan'adam da ya tsara masa rayuwarsa da hikimarsa da iliminsa da tsarkake shi daga riƙon ɗa.
• Wa'azi ga masu bijire wa ayoyin Alƙur'ani, masu ƙaryata addinin gaskiya suna kafirce wa ni'imomin da Allah ya yi musu, kuma da sannu za su gamu da azabarsa tun daga lokacin da mutuwa za ta zo musu.
• Fito da wautar mushirikai a fili masu neman sai Annabi ya zo musu da wasu mu'ujizoji da suka zayyana, tare da rushe hujjarsu ta cewa Allah ne ya ga damar su yi shirka shi ne ya sa suke yi, domin wai su ƙure Manzon Allah (ﷺ) da bayanin mene ne haƙiƙanin *mashi'a* ta Allah da tabbatar da gaskiyar Alƙur'ani domin ma'abota Littafi sun san cewa shi gaskiya ne.

• Sukan mushirai a kan ƙaryata tashi bayan mutuwa da suke yi da tabbatar musu da cewa wannan abu ne da zai auku babu makawa, inda za su haɗu da azabar Allah, abubuwan da suke bauta wa su yi barambaram da su a yayin da ba za su amfane su da komai ba.
• Surar ta ƙunshi lallashin Manzon Allah (ﷺ) da ƙarfafar zuciyarsa da kiran sa zuwa ga haƙurin ɗaukar nauyin da Allah ya ɗora masa ba tare da nuna gajiya ko ƙosawa ba.
• Bayanin cewa hikimar da ta sa Allah ya aiko da manzanninsa ita ce gargaɗi da albishir, ba wai don su riƙa ba wa mutane labaran gaibu waɗanda suke neman sani a wurinsu ba, domin sanin gaibu na Allah ne shi kaɗai.
• Bayanin cewa masu karɓa kiran Allah su ne waɗanda suke jin wa'azi su yi aiki da shi, zukatansu su rayu. Amma masu matattun zukata waɗannan wa'azi ba ya ratsa su.
• Hana zama tare da masu kutse cikin ayoyin Allah suna ƙaryata su, da yin umarnin a bijire wa mushurikai, amma kada a zagi abin da suke bauta wa ba Allah ba.
• Kwatanta misalin Annabi Muhammadu (ﷺ) da mutanesa da na Annabi Ibrahimu da mahaifinsa tare da mutanensa wajen faɗa da gaskiya. Kuma duk annabawa kamar haka suka rayu.
• Da sauran mahimman batutuwa da Surar ta ƙunsa

Suratul An’am (1-3)

ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَجَعَلَ ٱلظُّلُمَٰتِ وَٱلنُّورَۖ ثُمَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمۡ يَعۡدِلُونَ ١ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَكُم مِّن طِينٖ ثُمَّ قَضَىٰٓ أَجَلٗاۖ وَأَجَلٞ مُّسَمًّى عِندَهُۥۖ ثُمَّ أَنتُمۡ تَمۡتَرُونَ ٢ وَهُوَ ٱللَّهُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ يَعۡلَمُ سِرَّكُمۡ وَجَهۡرَكُمۡ وَيَعۡلَمُ مَا تَكۡسِبُونَ ٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Wanda Ya halicci sammai da ƙasa, kuma Ya halicci duffai da haske; sannan waɗanda suka kafirta suna daidaita Ubangijinsu da (wasu).

2. Shi ne Wanda Ya halicce ku daga taɓo, sannan Ya yanka (muku) ajali; da kuma wani ajalin sananne a wurinsa; sannan sai ga shi kuna jayayya.

3. Kuma Shi ne Allah a cikin sammai da kuma cikin ƙasa; Yana sane da abin da kuke ɓoyewa da abin da kuke bayyanawa, kuma Yana sane da abin da kuke aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da bayyana cikakken yabo da godiya marar iyaka ta tabbata gare shi shi kaɗai, domin shi ne wanda ya halicci sammai da ƙasa, kuma ya halicci duffai da haske; wannan ya ƙunshi duhun dare da hasken yini da duhun jahilci da hasken ilimi da duhun shirka da saɓon Allah da hasken imani da ɗa’a ga Allah. Amma duk da haka kafirai suna daidaita Allah da wasu abubuwan da suke bauta wa, duk kuwa da cewa sun yarda waɗannan ba su halicci komai ba.
Sannan ya bayyana cewa, shi ne ya halicci mutane da taɓo, ta hanyar halittar mahaifinsu Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya kuma iyakance musu lokacin rayuwarsu ta duniya, sannan ita ma duniya ya iyakance mata lokacinta, wanda bayan ƙarewarsa za ta gushe gaba ɗayanta; wannan lokacin kuwa babu wanda ya san shi sai Allah shi kaɗai. Bayansa kuma sai lokacin tashi daga ƙabari domin yin hisabi da saka wa kowa da ayyukansa. To amma duk da irin wannan bayani, kafirai ba su daina shakkar al’amarin lahira ba.

Sai kuma ya bayyana cewa, shi ne Allah abin bauta a sammai da ƙasa, yana sane da abin da bayinsa suke ɓoyewa da wanda suke bayyanawa, kuma yana sane da duk abin da suke aikatawa na alheri ne ko na sharri, kuma yana ƙididdige shi, kuma zai yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin haɗarin da yake tattare da bijire wa ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Kira zuwa ga lura da yin izina daga al'ummomin da suka gabata. Sunnar Allah kuma ta gudana a kan halaka duk wata al'umma da ta ƙaryata manzonta bayan ya bayyana musu gaskiya sun ƙi bin ta.

3. Waɗanda suka bijire wa kiran Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sau tari suna yin haka ne bayan sun ga hujjoji da dalilai waɗanda za su sanya su su yi imani, su yarda da gaskiyar mai kiran su zuwa ga Allah, su yarda da cewa Allah Ɗaya ne, shi ne kuma wanda ya cancanci a bauta wa, amma saboda gardama da taurin kai sai su ƙaryata su.

4. Bayanin rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa, ta yadda ba ya kama su da laifi ko ya yi musu azaba, har sai ya bayyana musu ayoyinsa da dalilai masu nuna musu gaskiya, to idan sun bijire ne, sai ya kama su da azabarsa.

5. Bayanin girman Kudurar Allah da kishinsa, yadda ya halaka masu ƙaryata ayoyinsa duk da ƙarfinsu da ni'imar da suke cikinta.

6. Zunubi yana jawo fushin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma Allah yana iya halaka al'umma saboda yawan zunubanta.

7. Halaka wata al'umma da ta saɓa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ta bijire wa koyarwar annabawa, ba a bakin komai yake a wurin Allah ba, wannan mai sauƙi ne a wurinsa ya halaka su, ya kawo waɗanda za su maye gurbinsu.

8. Ishara ga mushirikai cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya kawar da su, ya danƙa mulkinsu a hannuwan Musulmi, ya mallaka musu gidajensu da garuruwansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu hakan lokacin da Annabi (ﷺ) da sahabbansa suka buɗe garin Makka.

Suratul An'am (4-6)

وَمَا تَأۡتِيهِم مِّنۡ ءَايَةٖ مِّنۡ ءَايَٰتِ رَبِّهِمۡ إِلَّا كَانُواْ عَنۡهَا مُعۡرِضِينَ ۝٤ فَقَدۡ كَذَّبُواْ بِٱلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمۡ فَسَوۡفَ يَأۡتِيهِمۡ أَنۢبَٰٓؤُاْ مَا كَانُواْ بِهِۦ
يَسۡتَهۡزِءُونَ ۝٥ أَلَمۡ يَرَوۡاْ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا مِن قَبۡلِهِم مِّن قَرۡنٖ مَّكَّنَّٰهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ مَا لَمۡ نُمَكِّن لَّكُمۡ وَأَرۡسَلۡنَا ٱلسَّمَآءَ عَلَيۡهِم مِّدۡرَارٗا وَجَعَلۡنَا
ٱلۡأَنۡهَٰرَ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمۡ فَأَهۡلَكۡنَٰهُم بِذُنُوبِهِمۡ وَأَنشَأۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِمۡ قَرۡنًا ءَاخَرِينَ ۝٦

4. Kuma babu wata aya cikin ayoyin Ubangijinsu da za ta zo musu, face sai sun kasance masu bijire mata.

5. To haƙiƙa sun ƙaryata gaskiya lokacin da ta zo musu; don haka da sannu labaran abin da suka kasance suna izgili da shi zai zo musu.

6. Shin ba su ga yawan al'ummun da Muka halakar a gabaninsu ba, waɗanda Muka kafa su a banƙasa suka yi ƙarfi irin kafawar da ba Mu yi muku ba, kuma Muka aiko musu da ruwan sama a kai a kai, kuma Muka sanya ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu, sai Muka hallakar da su saboda zunubansu, kuma bayan shuɗewarsu Muka halicci wata sabuwar al'ummar daban?

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana a kan Tauhidi, wato kaɗaita shi da bauta, da kuma tashin alƙiyama, sai kuma a waɗannan ayoyi yake bayanin tabbatar da annabci, tare da bayanin halayen kafirai waɗanda duk wata hujja da wani dalili da za a kawo musu don tabbatar da kaɗaitakar Allah da gaskiyar manzanninsa, sai sun sa ƙafa su shure shi, su kuma ƙaryata gaskiya bayan ta zo musu daga Allah. To su kwana da sanin cewa, wata uƙubar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tana nan tafe a kansu, saboda izgili da shaƙiyanci da suke yi wa gaskiya da waɗanda suka zo da ita.
Yanzu ashe ba su ga yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa al'ummomin da suka gabace su ba? Ba su ga yawan waɗanda Allah ya halakar a cikinsu ba, waɗanda Allah ya ba su cikakken iko a bayan ƙasa irin wanda bai ba wa waɗannan kafiran na zamanin Manzon Allah ba? Allah ya ba su ƙarfin jiki da yawan dukiya da 'ya'ya, kamar yadda ya nuna a cikin *Suratur Rum*, aya ta 9-10, da Suratus *Saba'i*, aya ta 45. Sannan ya hore musu albarkacin ruwan sama wanda ba ya yankewa, ya sanya ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashin gidajensu. To amma duk da haka ya halaka su saboda zunubansu, ya kawo wasu mutanen daban bayansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba wai don rashin ƙaƙƙarfan dalili ne ya sa kafirai suke ƙin ba da gaskiya ba; girman kai ne da jayayya suka hana su miƙa wuya ga gaskiya.

2. Bayani a kan cewa saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana daga cikin dalilan saukar azabar Allah, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa kowane mai laifi uƙuba daidai da laifinsa.

3. Kafiran zamanin Manzon Allah (ﷺ) sun yi imani da cewa akwai mala'iku.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya bayyanar da wata aya ko mu'ujiza saboda kawai wasu mutane sun buƙaci a bayyanar da ita; yana bayyana ayarsa ne a duk sanda ya ga dama, babu mai yi masa tilas.

5. Bayanin rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya aiko jinsin mutum zuwa ga 'yan'uwansa mutane. Da a ce ya aiko da mala'ika ne, to da mutane za su riƙa yin imani ne saboda tsoro da firgici ba don sun fahimci gaskiya ba, da kuma ba su samu nutsuwar kusantarsa da koyon addininsu a wajensa ba.

6. Mutane ba za su iya jure kallon mala'ika a cikin kamanninsa na mala'ika ba; hasalima kaɗan ne daga cikin annabawa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su ikon ganin mala'ika a surarsa ta mala'ika.

7. Karantar da Annabi (ﷺ) al'adar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) game da annabawansa da alaƙarsu da al'ummominsu da lallashin sa a kan abin da mutanensa suke nuna masa na taurin kai da ƙaryatawa da kuma kwantar masa da hankali ta hanyar yi masa bayanin irin uƙubar da ya tanadar wa masu izgili ga annabawa.

8. Yin izgili da rashin kunya ga masu faɗar gaskiya yana jawo matsananciyar azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

9. Umarni da yin yawo a bayan ƙasa don ganin yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa al'ummomin da suka ƙaryata manzanni da ɗaukar izina da wa'azi daga halayensu.

Suratul An'am (7-11)

وَلَوۡ نَزَّلۡنَا عَلَيۡكَ كِتَٰبٗا فِي قِرۡطَاسٖ فَلَمَسُوهُ بِأَيۡدِيهِمۡ لَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ مُّبِينٞ ٧ وَقَالُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ مَلَكٞۖ وَلَوۡ أَنزَلۡنَا مَلَكٗا لَّقُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ ثُمَّ لَا يُنظَرُونَ ٨ وَلَوۡ جَعَلۡنَٰهُ مَلَكٗا لَّجَعَلۡنَٰهُ رَجُلٗا وَلَلَبَسۡنَا عَلَيۡهِم مَّا يَلۡبِسُونَ ٩ وَلَقَدِ ٱسۡتُهۡزِئَ بِرُسُلٖ مِّن قَبۡلِكَ فَحَاقَ بِٱلَّذِينَ سَخِرُواْ مِنۡهُم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ١٠ قُلۡ سِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ ثُمَّ ٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ١١

7. Kuma in da Mun saukar maka da wani littafin a rubuce a takardu, har suka taɓa shi da hannayensu, lalle da waɗanda suka kafirta sun ce: "Wannan ba komai ba ne, face sihiri bayyananne."

8. Kuma suka ce: "Don me ba a saukar masa da mala'ika ba?" Da kuwa Mun saukar da mala'ikan, to da ta faru ta ƙare (an hallaka su), sannan ba za a saurara musu ba.

9. Kuma in da Mun yo shi mala'ika ne, to lalle da Mun mayar da shi mutum, kuma da lalle Mun rikitar da su kamar yadda suka rikitar da kansu.

10. Kuma haƙiƙa an yi wa waɗansu manzanni da suka gabace ka izgili, sai sakamakon abin da suka kasance suna yin izgili da shi ya sauka kan masu izgilin.

11. Ka ce: "Ku yi tafiya a bayan ƙasa, sannan ku duba ku ga, yaya ƙarshen lamarin masu ƙaryatawa ya kasance?"

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana irin yadda kafirai suka kai matuƙa wajen ƙaryata gaskiya da ƙaryata Annabi (ﷺ) wanda ya zo musu da ita, ta yadda komai ƙarfin hujjar da za su gani ba za su yi imani ba, domin idanunsu sun rufe, suna so su ga bayan Manzon Allah (ﷺ) ko ta halin ƙaƙa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi bayanin cewa, da zai saukar wa Annabi (ﷺ) maganarsa a rubuce a takarda, kafirai su kama takardar da hannunsu, to da duk da haka sai sun ci gaba da jayayya da taurin kai, da kuma sun ce wannan abu ai sihiri ne, rufa-ido ne. Kuma sun ci gaba da nuna wa Annabi (ﷺ) taurin kai, har ma suka ce wai me ya hana a saukar da wani mala'ika tare da shi, yana gaskata shi idan ya faɗi wata magana, yana taimaka masa idan ya nemi taimako? Sai Allah ya mayar musu da martani cewa, da a ce Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da mala'ika kamar yadda suke buƙata, to da tuni azabar Allah ta sauka a kansu in sun ƙi yin imani, da ba za a jinkirta musu har su tuba ba.
Ubangiji kuma ya ƙara tabbatar musu cewa, babu wani amfani a saukar da wani mala'ika yana gaskata Annabi (ﷺ), yana umarnin mutane su bi shi, domin ko da ya saukar da shi ne to zai saukar da shi ne cikin surar mutum irinsu, domin su iya kusantarsa su saurari abin da yake faɗa musu ba tare da sun ji wani tsoro ba. Kuma da ya saukar da mala'ika da surarsa, da ba za su iya tsayawa suna kallon sa ba; idan kuma ya saukar da shi a kamanni irin nasu na mutane to da al'amarinsa ya sake rikice musu sun ce su ba su yarda mala'ika ne ba, kamar yadda suka sanya wa kansu rikici ba gaira-ba dalili game da sha'anin Manzon Allah (ﷺ), suka ce su ba za su yarda a aiko musu mutum irinsu ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rarrashi Annabi (ﷺ) da cewa, ai an yi wa manzannin da suka gabace shi izgili, sai Allah ya saukar da uƙubarsa a kan waɗannan masu izgilin. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya faɗa wa waɗannan masu ƙaryata shi cewa, me zai hana su yi tafiya a bayan ƙasa, su shiga duniya su gano kufaifai na al'ummomin da suka gabata, waɗanda suka ƙaryata

manzanninsu, sannan su duba su ga yadda ƙarshensu ya kasance, su ga irin halakar da ta same su da yadda Allah ya rushe gidajensu, don haka su ɗauki izina da wa’azi daga gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da dalili a kan cewa, Allah ne kaɗai ya cancanta a bauta masa domin shi ne mahaliccin sammai da ƙasa ba wani ba.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana wajabta wa kansa abin da ya ga dama, babu mai yi masa tilas.

3. Rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ita take tattare da komai.

4. Yana daga cikin rahamar Allah, bayyana wa bayinsa dalilai masu nuna gaskiyar zuwan ranar alƙiyama don mutane su yi imani, su yi ayyuka na ƙwarai, su guji munanan ayyuka.

Suratul An’am (12-13)

قُل لِّمَن مَّا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ قُل لِّلَّهِۚ كَتَبَ عَلَىٰ نَفۡسِهِ ٱلرَّحۡمَةَۚ لَيَجۡمَعَنَّكُمۡ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ لَا رَيۡبَ فِيهِۚ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ فَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ١٢ وَلَهُۥ مَا سَكَنَ فِي ٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ١٣

12. Ka ce: “Abin da yake cikin sammai da ƙasa na wane ne?” Ka ce: “Na Allah ne.” Ya wajabta wa kansa yin rahama. Lalle tabbas zai tattara ku zuwa ranar tashin alƙiyama wadda babu kokwanto game da ita. Waɗanda suka yi hasarar kawunansu ba za su yi imani ba.

13. “Kuma abin da ya nutsu a cikin dare ko rana nashi ne, kuma Shi ne Mai ji, Mai yawan sani.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya tambayi masu ƙaryata shi cewa, mallakar duk abin da yake sammai da ƙasa na wane ne? Sannan ya umarce shi da ya ba da amsar wannan tambayar, ya ce musu: Mallakar wannan gaba ɗaya ta Allah ce, wanda shi ne ya cancanta a bauta masa shi kaɗai. Kuma ya wajabta wa kansa yin rahama wadda ta yalwaci kowa da komai.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Yayin da Allah ya yi halitta ya rubuta a littafi wanda yake wurinsa a saman Al-arshi: “Lalle rahamata ta rinjayi fushina.” [Bukhari #7404, da Muslim #2715].

Allah kuma ya yi alƙawarin lalle zai tattara mutane gaba ɗaya, a ranar alƙiyama wadda babu kokwanto a cikinta. Kuma masu hasara na haƙiƙa su ne waɗanda suka tozarta kawunansu a duniya, ba su yi imani ba. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, duk wani abu da ya nutsu a mahallinsa da daddare ne ko da rana, to mallakarsa ne, halittarsa ne, komai a ƙarƙashin ikonsa yake (Mai tsarki da ɗaukaka), shi kuma mai jin duk wani sauti ne, kuma masanin komai ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kada bawa ya nemi mafaka a wurin kowa in ba a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba, domin shi ne majiɓincin lamarin bayinsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda ya ƙirƙiri halittar sammai da ƙassai shi ne kawai wanda ya cancanta bawa ya riƙe, ya nemi taimakonsa da agajinsa a koyaushe.

3. Allah (mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai ciyarwa, babu mai iya ba wa kowa komai sais hi, don haka mu nemi arzikinmu a wurinsa, babu mai hana abin da ya bayar, babu kuma mai bayar da abin da ya hana.

4. Allah (mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa Muhammadu (ﷺ) da ya bayyana cewa, ba shi da wani majiɓinci ba Allah ba, domin shi ne shugaba wanda ake koyi da shi, don haka wajibi ne ya tabbatar da Rububiyya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Saɓon Allah shi ne yake jawo azabar Allah. Saɓon Allah iri biyu ne: Saɓon da Allah ba ya gafarta shi, shi ne yin shirka da Allah. Na biyu, saɓon da Allah yake gafarta shi ga wanda ya ga dama, su ne kaba'ira. Akwai saga'ira, wato ƙananan saɓo waɗanda kyawawan ayyuka ne suke kankare su.

6. Wannan addinin shi ne addinin Allah na gaskiya, babu wanda ya fi ƙarfin a hukunta shi idan ya yi ba daidai ba komai matsayinsa, kuma ranar sakamako rana ce da dukiya da 'ya'ya ba za su amfani bawa ba sai aikinsa na ƙwarai.

Suratul An'am (14-16)

قُلْ أَغَيْرَ ٱللَّهِ أَتَّخِذُ وَلِيًّا فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَهُوَ يُطْعِمُ وَلَا يُطْعَمُ ۗ قُلْ إِنِّيٓ أُمِرْتُ أَنْ أَكُونَ أَوَّلَ مَنْ أَسْلَمَ ۖ وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٤﴾ قُلْ إِنِّيٓ أَخَافُ إِنْ عَصَيْتُ رَبِّي عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿١٥﴾ مَّن يُصْرَفْ عَنْهُ يَوْمَئِذٍ فَقَدْ رَحِمَهُۥ ۚ وَذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْمُبِينُ ﴿١٦﴾

14. Ka ce: "Shin yanzu wanin Allah ne zan riƙa a matsayin majiɓinci, alhalin Shi ne Ya halicci sammai da ƙasa, kuma Shi Yake ciyarwa, ba a ciyar da Shi?" Ka ce: "Lalle ni an umarce ni da in zamo farkon mai miƙa wuya; kuma lalle kada ka kasance daga masu shirka."

15. Ka ce: "Lalle ni ina jin tsoron azabar rana mai girma, idan na saɓa wa Ubangijina."

16. Wanda duk aka kawar masa da (azaba) a wannan rana, to haƙiƙa (Allah) Ya ji ƙan sa. Kuma wannan Shi ne rabo mabayyani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya ce: Yanzu shi za a ce ya riƙi wani ba Allah ba a matsayin majiɓincin lamarinsa, yana mai neman taimako da agaji a wurinsa ba Allah ba, alhalin kuwa ya san Allah ne mahaliccin sammai da ƙasa ba tare da ya kwaikwaya a wurin wani ba, kuma shi mawadaci ne, ba shi da buƙata a wurin kowa cikin halittunsa, kuma shi ne mai arzuta su, ya ciyar da su, ba tare da shi ya buƙaci ciyarwarsu ba? To sai Allah ya umarci Manzonsa da ya faɗa musu cewa, shi kam Ubangijinsa ya umarce shi da ya zama farkon mai miƙa wuya a gare shi, kuma an hana shi zama ɗaya daga cikin mushirikai masu haɗa Allah da wani abu wajen bauta. Kuma ya faɗa musu cewa, shi yana jin tsoron azabar Ubangijinsa ranar gobe ƙiyama. Wannan azabar tasa mai tsanani kuwa duk wanda aka kautar masa da ita ranar alƙiyama, to haƙiƙa Allah ya yi masa babbar rahama, kuma wannan shi ne rabo na haƙiƙa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne a kan mumini ya mayar da fatansa zuwa ga Allah shi kaɗai.

2. Wajibi ne mumini ya yi imani da cewa Allah ne kaɗai mai amfanarwa, mai cutarwa, babu mai iya yi maka abin da Allah bai yi maka ba, kuma babu mai hana abin da Allah ya yi maka.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sama da bayinsa da Zatinsa da siffofinsa da sunayensa da ayyukansa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fi ƙarfin duk wani mai ƙarfi, kuma ƙarfinsa haɗe yake da cikakken ilimi da cikakkiyar hikima.

5. Duk wanda saƙon Alƙur'ani ya je masa, ya fahimci kiran da ke cikinsa, to hujja ta tsaya a kansa.

6. Babbar manufar saukar da Alƙur'ani ita ce gargaɗi da bushara, wato kira zuwa ga hanyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

7. Annabi (ﷺ) Manzo ne zuwa ga dukkan talikai.

8. Wautar mushirikai masu bauta wa wanin Allah da bayar da shaida a kan bautarsa, duk da cewa sun yarda babu wanda ya yi halitta sai Allah shi kaɗai.

Suratul An'am (17-19)

وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ وَإِن يَمۡسَسۡكَ بِخَيۡرٖ فَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١٧ وَهُوَ ٱلۡقَاهِرُ فَوۡقَ عِبَادِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡحَكِيمُ ٱلۡخَبِيرُ ١٨ قُلۡ أَيُّ شَيۡءٍ أَكۡبَرُ شَهَٰدَةٗۖ قُلِ ٱللَّهُۖ شَهِيدُۢ بَيۡنِي وَبَيۡنَكُمۡۚ وَأُوحِيَ إِلَيَّ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ لِأُنذِرَكُم بِهِۦ وَمَنۢ بَلَغَۚ أَئِنَّكُمۡ لَتَشۡهَدُونَ أَنَّ مَعَ ٱللَّهِ ءَالِهَةً أُخۡرَىٰۚ قُل لَّآ أَشۡهَدُۚ قُلۡ إِنَّمَا هُوَ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞ وَإِنَّنِي بَرِيٓءٞ مِّمَّا تُشۡرِكُونَ ١٩

17. Kuma idan Allah Ya shafe ka da wata cuta, to ba wanda ya isa ya yaye ta sai Shi; kuma idan Ya shafe ka da wani alheri, to Shi Mai iko ne a kan komai.

18. Kuma Shi ne Mai rinjaye a kan bayinsa. Kuma Shi Mai hikima ne, Masani.

19. Ka ce: "Mene ne mafi girman shaida?" Ka ce; "Allah Shi ne shaida tsakanina da ku. Kuma an saukar mini wannan Alƙur'anin ne don in yi muku gargaɗi da shi da kuma duk wanda zai isa zuwa gare shi. Yanzu kuwa za ku shaida cewa, lalle akwai waɗansu allolin tare da Allah?" Ka ce: "Ni kam ba zan shaida ba." Ka ce: "Allah Shi Ɗaya ne, kuma lalle ni ba ruwana da dukkan abin da kuke haɗa Allah da shi."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, idan Allah ya nufi bawa da wata cuta, to babu mai raba shi da ita sai shi; idan kuma ya nufe shi da samun wani alheri, kamar lafiya ko ilimi ko dukiya ko 'ya'ya, to shi mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gagarar sa, kuma ba wanda zai iya hana wannan alheri ya same shi ko ya raba shi da shi sai shi kaɗai.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance idan ya ɗago daga ruku'u sai ya ce: "Ya Ubangijinmu, yabo da godiya sun tabbata a gare ka cikin sammai da ƙasa da cikin abin da ka ga dama bayansu, kai ne ka cancanci yabo da girmamawa; wannan shi ne mafi cancantar abin da bawa ya faɗa, dukkan mu bayinka ne. Ya Allah, babu mai hana abin da ka bayar, kuma babu mai bayar da abin da ka hana; wadatar mai wadata ba za ta amfane shi a wurinka ba." [Muslim #477].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "...Ka sani, da a ce dukkan al'umma za su haɗu a kan su amfanar da kai da wani abu, to ba za su amfanar da kai da komai ba sai abin da Allah ya rubuta maka. Hakanan da za su taru a kan su cuce ka da wani abu, to ba za su cuce ka da komai ba sai da abin da Allah ya riga ya rubuta maka…." [Tirmizi #2516, da Ahmad #2669].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikar Kudurarsa da girman ikonsa, wato shi ne wanda ya fi ƙarfin kowa da komai, kuma shi ne maɗaukaki a saman halittunsa, ɗaukaka ta Zati da daraja da iko cikakke a kan bayinsa, kuma shi ne mai cikakkiyar hikima, mai cikakken sani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa Muhammadu (ﷺ) ya tambayi masu ƙaryata shi, wane abu ne ya fi girman shaida a kan gaskiyar da ya zo da ita? Kuma Allah ya umarce shi ya ba da amsa da cewa, shaidar da ta fi kowacce girma ita ce shaidar Allah, shi ne wanda kuskure ko mantuwa ko ƙarya ba sa faruwa a cikin shaidarsa, don haka shi ne shaida tsakaninsa da su, kuma shi ne wanda ya yi masa wahayin Alƙur'ani don ya yi musu gargaɗin azaba da shi, kuma ya gargaɗi duk wanda Alƙur'ani ya je masa. Kuma ya umarce shi ya tambayi waɗannan masu ƙaryatawar: Shin su ma za su yi shaida cewa, a tare da Allah akwai wasu ababen bauta? Idan sun bayar da irin wannan shaidar, to ya faɗa musu cewa, shi ba zai yi irin wannan shaidar tare da su ba. Abin bauta guda ɗaya ne tak, shi ne kaɗai ya cancanci a bauta masa, kuma shi Manzo (ﷺ) ba ruwansa da mushirikai masu haɗa Allah da wani wajen bauta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mafi girman zalunci shi ne mutum ya yi wa Allah ƙarya. Yana daga cikin yi wa Allah ƙarya, a jingina masa ɗa ko mata ko kishiya.

2. Wajibi ne ga mumini ya gaskata kowace aya ta Allah, watau ta halitta da ta shari'a, da kuma mu'ujizojin da Allah ya ba wa annabawa da manzanni da kuma hukunce-hukunce na imani da shari'a da ya saukar musu.

3. Azzalumi ba zai taɓa samun nasara ba, duk abin da zai samu ta hanyar zalunci ƙarshensa nadama ce da hasara.

4. Malaman Yahudawa sun san gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ) sarai, don haka ba su da wata hujja a wurin Allah ranar alƙiyama.

5. Duk wani abin bauta ba Allah ba, ba zai amfani masu bautarsa ba a ranar alƙiyama, domin bautarsu hanyar halaka ce, babu amfani a cikinta.

6. Mushirikai za su sharara ƙarya a ranar alƙiyama lokacin da za su ga gaskiyar abin da ake faɗa musu a fili; duk kuwa da cewa ƙarya a wannan lokaci ba ta da wani amfani, to amma saboda wanda ya tsinci kansa cikin ƙunci irin wannan yakan kiɗime, ya riƙa furta abin da ma ba zai amfane shi da komai ba.

ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَعۡرِفُونَهُۥ كَمَا يَعۡرِفُونَ أَبۡنَآءَهُمُۘ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ فَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ٢٠ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوۡ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ٢١ وَيَوۡمَ نَحۡشُرُهُمۡ جَمِيعٗا ثُمَّ نَقُولُ لِلَّذِينَ أَشۡرَكُوٓاْ أَيۡنَ شُرَكَآؤُكُمُ ٱلَّذِينَ كُنتُمۡ تَزۡعُمُونَ٢٢ ثُمَّ لَمۡ تَكُن فِتۡنَتُهُمۡ إِلَّآ أَن قَالُواْ وَٱللَّهِ رَبِّنَا مَا كُنَّا مُشۡرِكِينَ٢٣ ٱنظُرۡ كَيۡفَ كَذَبُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡۖ وَضَلَّ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ٢٤

20. Waɗanda Muka ba su Littafi sun san shi kamar yadda suka san ‘ya’yansu. Waɗanda suka yi hasarar kawunansu, to su kam ba za su taɓa yin imani ba.

21. Kuma ba mafi zalunci fiye da wanda ya ƙirƙiri ƙarya ya jingina wa Allah, ko kuma ya ƙaryata ayoyinsa. Haƙiƙar lamarin dai su azzalumai ba za su taɓa rabauta ba.

22. Kuma (ka tuna) ranar da za Mu tattara su gaba ɗaya, sannan Mu ce da waɗanda suka yi shirka: “Ina abokan tarayyarku waɗanda kuka kasance kuna riyawa?”

23. Sannan fitinarsu ba ta zamo komai ba, face cewar da suka yi: “Wallahi, ya Ubangijinmu, ba mu kasance masu yin shirka ba!”

24. Duba ka ga yadda suka yi wa kansu ƙarya. Kuma abin da suka kasance suna ƙirƙira ya ɓace musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, Yahudawa da aka ba su littafin Attaura da Nasara da aka ba su littafin Linjila sun san Annabi Muhammadu (ﷺ) Annabin Allah ne, kuma Manzonsa ne, kamar yadda ɗayansu ya san ɗan cikinsa. Waɗanda suka tafka hasara su ne waɗanda suka kafirce wa Annabi (ﷺ), suka ƙi yin imani da shi da manzancinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu wani babban azzalumi kamar wanda ya yi wa Allah ƙarya, ko kuma ya ƙaryata hujjojin da Allah ya saukar. Kuma lalle har abada azzalumai ba za su rabauta ba. Allah kuma zai tashi mushirikai gaba ɗaya a ranar alƙiyama, ya tambaye su, ina ababen tarayyarsu da suka ɗauke su a matsayin alloli, suna bauta musu? To a wannan tambayar dai ba su da wata amsar da za su bayar mai gamsarwa, sai kawai su fara rantsuwa da Allah cewa, ai su ba su taɓa zama mushirikai ba, a rayuwarsu ta duniya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ankarar da Annabi (ﷺ) da ya dubi yadda waɗannan mutane suka yi wa kawunansu ƙarya a ranar alƙiyama, kuma suka nemi abubuwan da suka bauta wa ba Allah ba a duniya suka rasa, sun ɓace musu ɓat, ba su amfane su da komai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ga mai sauraron ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi sauraro na fahimtar abin da aka karanta masa don ya yi aiki da shi a rayuwarsa.

2. Duk mai jayayya da gaskiya da niyyar ya ɓata ta, Allah yana hana masa fahimtar ayoyinsa, yana kuma toshe masa ƙofofin samun ilimi mai amfani.

3. Rashin imanin kafirai da Annabi (ﷺ) ba don rashin gamsasshiyar hujja ba ce; saboda taurin kai ne da ƙiyayya kawai.

4. Duk sanda maɓarnata suka kasa kayar da gaskiya ta hanyar hujja sai su riƙa kiran ta da sunan ɓatanci domin su jefa ƙin ta a zukatan masu sauraronsu.

5. Canza wa gaskiya suna ba ya kawar da ita daga haƙiƙaninta. Gaskiya tana nan muhallinta komai sauyin da aka yi mata.

6. Daga cikin kafirai akwai waɗanda kafircinsu bai taƙaita a kansu su kaɗai ba; sukan yi iya ƙoƙarinsu su ga sun hana sauran mutane karɓar gaskiya, waɗannan su ne kafircinsu ya fi tsanani.

7. Sau tari wasu sukan jefa kansu cikin halaka ba tare da sun sani ba.

Suratul An'am (25-26)

وَمِنْهُم مَّن يَسْتَمِعُ إِلَيْكَ ۖ وَجَعَلْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ وَفِيٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرًا ۚ وَإِن يَرَوْا۟ كُلَّ ءَايَةٍ لَّا يُؤْمِنُوا۟ بِهَا ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوكَ
يُجَـٰدِلُونَكَ يَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ إِنْ هَـٰذَآ إِلَّآ أَسَـٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٢٥﴾ وَهُمْ يَنْهَوْنَ عَنْهُ وَيَنْـَٔوْنَ عَنْهُ ۖ وَإِن يُهْلِكُونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿٢٦﴾

25. Kuma daga cikinsu akwai wanda yake sauraren ka; kuma Mun sanya murafai a zukatansu, ta yadda ba za su iya fahimtar sa ba, haka kuma a kunnuwansu akwai wata toshiya. Kuma in da za su ga kowace irin aya ce, ba za su yi imani da ita ba. Har ma idan sun zo maka suna jayayya da kai, (sai) waɗanda suka kafirta su riƙa cewa: "Ai wannan ba komai ba ne face tatsuniyoyin mutanen farko."

26. Kuma suna hana (mutane) sauraren sa (Alƙur'ani), kuma su kansu suna ƙara nesanta da shi; kuma ba kowa suke hallakarwa ba face kawunansu, sai dai su ba sa jin hakan.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana nusantar da Annabi (ﷺ) cewa, mushirikai da yake yi wa wa'azi ba dare ba rana, a cikinsu akwai waɗanda ba za su taba yin imani ba duk kuwa da irin ƙarfafan hujjoji da ya zo musu da su. Kuma a cikinsu akwai waɗanda suke sauraron sa lokacin da yake karanta musu Alƙur'ani, amma fa ba sa amfana da komai daga ayoyinsa, domin kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rufe zukatansu ruf, ba sa fahimtar komai, ya doɗe kunnuwansu ba sa yin sauraro mai amfani, kuma Allah ya yi musu hakan ne saboda taurin kansu da jayayyarsu bayan sun ga hujjoji da dalilai a bayyane amma sun ƙi yin imani. Idan ma sun zo fadar Manzon Allah (ﷺ), ba wani abu yake kawo su ba sai don su yi ta jayayya da shi a kan gaskiyar da yake faɗa musu, har ma suna cewa, ai duk abin da ya zo da shi ya ɗauko shi ne daga littattafan tatsuniyoyin mutanen farko.
Allah (ﷺ) ya bayyana wa Manzonsa cewa, su waɗannan mushirikai ba wai kawai sun ƙi karɓar gaskiya ne a karan-kansu ba; suna ma hana mutane su karɓi gaskiyar bayan su sun guje ta; to amma ba kowa suke halakarwa ba sai kawunansu, kuma ba sa jin hakan ko a jikinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirai ba za su bar yin ƙarya ba har ma a lahira.

2. Kwaɗaitarwa a kan guje wa duniya da fifita lahira da ayyukanta. Guje wa duniya kuma ba ya nufin ƙaurace wa abin da yake da amfani ga mutane, ko ƙin abin da zai ciyar da rayuwar ɗan'adam gaba; gudun duniya yana nufin cire ƙyalƙyalinta daga zuciya da kauce wa ruɗinta da fifita lahira da yin aiki dominta.

3. Allah zai yi magana da kafirai a ranar alƙiyama a wasu wurare. Akwai kuma inda ba zai yi musu magana ba, kamar yadda ya zo a wasu ayoyi. [Dubi Suratul Baƙara, aya ta 174].

4. Malamai sun bambance tsakanin kalmar [] da kuma kalmar [لَهْوٌ], suka ce: Ta farko tana nufin wasa wanda ba zai shagaltar da mutum daga aikata wajibi ba, amma ta biyu tana nufin wargi wanda zai shagaltar da shi daga aikata wajibin da yake kansa. Shi ya sa wasu malamai suka ce kalmar farko ana amfani da ita don siffanta wasannin yara, ta biyu kuma wasannin manya mai ɗauke hankalin mutum daga kan abin da ya wajaba a kansa.

Wasu kuma suka ce, ana amafani da kalmar farko wajen bayanin wasan da ba shi da wani amfani, kamar wasan yara. Ta biyu kuma akan yi amfani da ita ne wajen bayanin wasan da yake mai amfani wani lokaci, to amma yakan iya shagaltar da mutum daga abin da ya dace ya yi. [Dubi, Ibn Ashur, *Tafsir*, Juzu'i na 4, Shafi na 197].

Suratul An'am (27-32)

وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذْ وُقِفُواْ عَلَى ٱلنَّارِ فَقَالُواْ يَٰلَيْتَنَا نُرَدُّ وَلَا نُكَذِّبَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّنَا وَنَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٢٧﴾ بَلْ بَدَا لَهُم مَّا كَانُواْ يُخْفُونَ مِن قَبْلُ ۖ وَلَوْ رُدُّواْ لَعَادُواْ لِمَا نُهُواْ عَنْهُ وَإِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿٢٨﴾ وَقَالُوٓاْ إِنْ هِىَ إِلَّا حَيَاتُنَا ٱلدُّنْيَا وَمَا نَحْنُ بِمَبْعُوثِينَ ﴿٢٩﴾ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذْ وُقِفُواْ عَلَىٰ رَبِّهِمْ ۚ قَالَ أَلَيْسَ هَٰذَا بِٱلْحَقِّ ۚ قَالُواْ بَلَىٰ وَرَبِّنَا ۚ قَالَ فَذُوقُواْ ٱلْعَذَابَ بِمَا كُنتُمْ تَكْفُرُونَ ﴿٣٠﴾ قَدْ خَسِرَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِلِقَآءِ ٱللَّهِ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَتْهُمُ ٱلسَّاعَةُ بَغْتَةً قَالُواْ يَٰحَسْرَتَنَا عَلَىٰ مَا فَرَّطْنَا فِيهَا وَهُمْ يَحْمِلُونَ أَوْزَارَهُمْ عَلَىٰ ظُهُورِهِمْ ۚ أَلَا سَآءَ مَا يَزِرُونَ ﴿٣١﴾ وَمَا ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَآ إِلَّا لَعِبٌ وَلَهْوٌ ۖ وَلَلدَّارُ ٱلْـَٔاخِرَةُ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ يَتَّقُونَ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿٣٢﴾

27. Da kuma za ka ga lokacin da ake tsayar da su a gaban wuta, sai su ce: "Kaiconmu, ina ma da za a mayar da mu (duniya), to da ba za mu sake ƙaryata ayoyin Ubangijinmu ba, kuma za mu zamanto cikin muminai."

28. A'a, ba haka ba ne, abin da suke ɓoyewa a da shi ne ya bayyana a gare su; kuma in da za a mayar da su, to da sun koma kan abin da aka hana su. Kuma lalle su tabbas maƙaryata ne.

29. Kuma suka ce: "Ba wata (rayuwa) sai rayuwarmu ta duniya, kuma mu ba waɗanda za a sake tashin mu ba ne."

30. Kuma in da za ka ga lokacin da aka tsayar da su a gaban Ubangjinsu; ya ce: "Shin ashe wannan ba gaskiya ne ba?" Sai su ce: "Gaskiya ne, muna rantsuwa da Ubangijinmu." Sai Ya ce: "To ku ɗanɗani azaba saboda abin da kuka kasance kuna yi na kafirci."

31. Haƙiƙa waɗanda suka ƙaryata haɗuwa da Allah sun yi hasara; har sai lokacin da alƙiyama ta zo musu ba zato ba tsammani, sai su ce: "Kaiconmu kan irin sakacin da muka yi a cikinta (duniya)," alhalin kuwa suna ɗauke da kayan laifukansu a bayansu. Ku saurara, abin da suka ɗauka na laifi ya munana matuƙa.

32. Kuma rayuwar duniya ba komai ba ce face wasa da sharholiya; kuma lalle gidan lahira shi ne mafi alheri ga waɗanda suke kiyaye dokokin (Allah). Shin ba za ku hankalta ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana nuna wa Annabi (ﷺ) irin halin da kafirai za su tsinci kawunansu ne a lahira, inda ya ce, da a ce zai ga lokacin da za a tattara waɗannan mushirikan ranar alƙiyama, a tsayar da su a gaban wutar Jahannama, tabbas da ya ga abin mamaki, lokacin da za su ga wutar Jahannama da abubuwan firgici da suke cikinta; lokacin za su fara nadama da raki, suna burin ina ma za a sake mayar da su duniya sai su yi imani da ayoyin Allah, su yi aiki nagari, su zamo daga cikin muminai. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaryata su da cewa, abin ba haka ne ba, yanzu sun ga dahir ne; abin da suke ɓoyewa a da ne ya bayyana ya fito sarari. A duniya suna ɓoye gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ) duk da cewa sun san gaskiyarsa, amma taurin kai da hassada sun hana su yin imani, to yau ga shi gaskiyar ta fito sarari kowa ya gan ta. Don haka ko da ma an dawo da su duniya, za su ci gaba ne da ƙaryatawa da saɓon Allah kamar yadda suka saba a baya, domin ƙarya suke yi da suke cewa za su yi imani idan sun sake komowa duniya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya daɗa fallasa wata ƙaryar da mushrikai suke yi a duniya na cewa wai babu wata rayuwa in ban da rayuwar duniya, kuma babu tashin alƙiyama balle wani abu hisabi. To sai Allah ya nuna wa Annabi (ﷺ) cewa, da a ce zai ga waɗannan maƙaryata a ranar alƙiyama lokacin da Allah zai tirke su a gabansa ya tambaye su: Shin har yanzu suna nan kan bakansu cewa, wannan tashin Alƙiyamar ba gaskiya ba ne? Sai nan take su yi rantsuwa da Allah Ubangijinsu su ce: Lalle gaskiya ne babu wani kokwanto a kai, domin sun ga dahir. Sai Allah ya ce musu: To ai yanzu kam sai su ɗanɗani azaba sakamakon kafircinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tabbatar da cewa, duk waɗanda suka ƙaryata ranar gamuwa da shi sun yi babbar hasara, kuma sai ranar ta zo musu kwatsam ba zato ba tsammani ne za su riƙa cizon yatsa da nadama a bisa sakaci da rayuwarsu da suka yi a baya, ba su yi wa wannan ranar wani tanadi ba, ga shi yau sun haɗu da Ubangijinsu, suna ɗauke da kayan zunubansu a bayansu; to tir da wannan irin dako na kayan zunubi da suke yi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu haƙiƙanin wannan rayuwa ta duniya wadda suka nuna tsananin sonta ido-rufe suka ƙi sauraron duk wata gaskiya da ake faɗa musu, Allah ya nuna cewa wannan rayuwar ta duniya ba komai ba ce illa wasa da wargi da sharholiya marar amfani. Amma shi gidan lahira shi ne ya fi alheri ga wanda ya yi taƙawa, ya kiyaye dokokin Ubangijinsa. Yanzu ashe masu ƙaryata gamuwa da Allah ba za su hankalta ba, su fahimci mece ce duniya kuma mece ce lahira?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Damuwar Annabi (ﷺ) a kan shiriyar al'ummarsa, takan kai shi ga shiga wani hali marar daɗi.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya hana Annabinsa damuwa ne don wani abu ba; sai don gudun kada damuwar ta jawo masa rashin haƙuri da dauriya, waɗanda ba sa cikin ɗabi'unsa.

3. Jayayya da hukunce-hukuncen Allah da bijire musu tsantsar kafirci ne, ko da kuwa mutum ya gaskata a zuciyarsa, domin ana yi wa mutum hukunci ne da abin da ya bayyana a zahiri, ba abin da ya ɓoye a zuciyarsa ba.

4. Kafiran Kuraishawa ba sa sukan Annabi (ﷺ) da cewa shi maƙaryaci ne, domin tun yana yaronsa suke kiran sa mai amana, mai gaskiya.

5. Ishara ga duk wani mai kira zuwa ga Allah cewa, hanyarsa cike take da ƙalubale iri-iri, domin haka hanyar annabawa take. Don haka sai sun haɗa da haƙuri da juriya kamar yadda annabawa suka yi, sannan ne taimakon Allah zai zo.

6. Allah ne kaɗai mai ba da nasara ba wani ba, don haka koyaushe a dogara da shi domin samun taimakonsa.

7. Duk sa’adda wani lamari ya yi tsanani, to tabbas sauƙi yana nan tafe bayansa ba da jimawa ba.

8. Babu wanda ya isa ya canza abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara, don haka zakaran da Allah ya nufa da yin cara, ko ana muzuru ana shaho sai ya yi. Hakanan kalmomin Allah da ya saukar a littattafansa babu wanda yake da hurumin canza su in ba shi ba, don haka ko wani ya canza wani abu na hukuncin Allah, ya sani ya yi a banza, da shi da babu duk ɗaya ne a wurin Allah.

9. Shiriya a hannun Allah take, shi yake shiryar da wanda ya ga dama, ya ƙatar da wanda ya ga damar ƙatarwa.

10. Hikimar Allah ce ta gudana da ya yi mutane iri biyu, mumini da kafiri, domin sai da aka tantance munin kafirci sannan kyawun Musulunci ya bayyana.

Suratul An’am (33-35)

قَدۡ نَعۡلَمُ إِنَّهُۥ لَيَحۡزُنُكَ ٱلَّذِي يَقُولُونَۖ فَإِنَّهُمۡ لَا يُكَذِّبُونَكَ وَلَٰكِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ يَجۡحَدُونَ ٣٣ وَلَقَدۡ كُذِّبَتۡ رُسُلٞ مِّن قَبۡلِكَ فَصَبَرُواْ عَلَىٰ مَا كُذِّبُواْ وَأُوذُواْ حَتَّىٰٓ أَتَىٰهُمۡ نَصۡرُنَاۚ وَلَا مُبَدِّلَ لِكَلِمَٰتِ ٱللَّهِۚ وَلَقَدۡ جَآءَكَ مِن نَّبَإِيٱلۡمُرۡسَلِينَ ٣٤ وَإِن كَانَ كَبُرَ عَلَيۡكَ إِعۡرَاضُهُمۡ فَإِنِ ٱسۡتَطَعۡتَ أَن تَبۡتَغِيَ نَفَقٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ أَوۡ سُلَّمٗا فِي ٱلسَّمَآءِ فَتَأۡتِيَهُم بِـَٔايَةٖۚ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَمَعَهُمۡ عَلَى ٱلۡهُدَىٰۚ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡجَٰهِلِينَ ٣٥

33. Haƙiƙa Muna da cikakkiyar masaniyar cewa, lalle irin abin da suke faɗa yakan baƙanta maka rai; to a gaskiya su ba kai suke ƙaryatawa ba, sai dai azzalumai suna jayayya ne da ayoyin Allah.

34. Kuma lalle haƙiƙa an ƙaryata waɗansu manzanni a gabaninka, sai suka yi haƙuri a kan ƙaryata su da aka yi, kuma an cutar da su, har sai da taimakonmu ya zo musu. Kuma babu wanda ya isa ya musanya kalmomin Allah. Kuma lalle haƙiƙa wani sashi na labarin manzanni ya zo maka.

35. Kuma idan bijirewarsu ta dame ka, to idan har kana iya haƙa rami a cikin ƙasa, ko kuma (ka samu) wani tsani ka hau sama, don ka zo musu da wata aya, (to ka yi hakan). Kuma in da Allah Ya ga dama, tabbas da Ya tara su gaba ɗaya a kan shiriya. Don haka kada ka kasance cikin jahilai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, yana sane da irin baƙaƙen maganganun da mushirikai suke faɗa masa waɗanda suke ƙata masa rai, ya tabbatar masa da cewa, ba fa shi ne suke ƙaryatawa ba kai-tsaye; sun yarda a zukatansu cewa gaskiya yake faɗa musu, to amma sai su fito a fili suna jayayya da shi domin su ƙaryata ayoyin Allah don tsabar girman kai da taƙewa.
To sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashe shi ta hanyar cewa, waɗannan abubuwan da yake gani daga mutanensa na baƙin ciki da ƙacin rai, irinsu ne annabawan da suke gabaninsa suka riƙa gani daga al’ummominsu, domin su ma an ƙaryata su, an cutar da su, to amma sai suka yi ta haƙuri har zuwa lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su nasara. Don haka shi ma Manzon Allah (ﷺ) sai ya ci gaba da haƙuri har lokacin da nasarar Allah za ta zo. Sai kuma ya bayyana cewa, waɗannan masu ƙaryata shi ɗin ba ɗaya daga cikinsu da ya isa ya canza kalmomin Allah waɗanda ya riga ya rubuta na tabbatar da

samun nasara ga Manzonsa (ﷺ). Sannan Allah ya tabbatar masa cewa, ai ya samu labaran manzanni da dama da suka shuɗe a gabaninsa da irin nasara da taimakon da ya yi musu.
Ya ci gaba da faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, idan har bijirewar waɗannan mushirikai gare shi tana damun sa ainun, to idan har zai iya samun wani rami a ƙarƙashin ƙasa ko wani tsani da zai hau sama, don ya je ya kawo musu wata hujja ko wani dalili da zai gamsar da su a kan gaskiyarsa, to yana iya yin hakan. To amma ya sani cewa, da Allah ya ga dama da ya tara su dukansu a kan shiriya, ba a samu mai fanɗarewa ko ɗaya daga cikinsu ba. Don haka sai ya ja hankalinsa da kada ya kasance cikin jahilai waɗanda ba su san yadda al'amura suke ba, ba su san yadda aikin Allah yake gudana a cikin halittunsa ba, wanda hakan ne zai saka shi ya ci gaba da damuwa a kan bijirewarsu da rashin imaninsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutumin da ya fi kowa sauraron Alƙur'ani, sauraro na fahimta, ya fi saurin karɓar saƙon da ke cikinsa.

2. Faɗakar da Musulmi a kan tausaya wa dabbobi, domin su ma al'ummomi ne kamar mu.

3. Duk wanda ya cutar da wata dabba ba da wani haƙƙi ba, to sai Allah ya yi hisabi a tsakaninsu ranar alƙiyama.

4. Kafirai sun nemi a saukar musu da wata aya ta musamman bayan ga Alƙur'ani suna gani, ba don komai ba sai don jayayya, su ga sun ƙure Annabi (ﷺ), domin Alƙur'ani shi ne babbar mu'ujiza da babu kamarta wadda ke nuna gaskiyar Annabi (ﷺ).

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne yake ba wa Annabi (ﷺ) kariya da kansa, shi ya sa duk sa'adda kafirai suka ƙalubalance shi da wani abu, to Allah ne yakan faɗa masa martanin da zai mayar musu.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai cikakken iko ne, babu abin da yake gagarar sa, don haka duk abin da kafirai suka nema ya yi idan bai yi ba, to ya ƙi yi ne saboda wata hikima da su ba su san ta ba.

7. Ya wajaba mutane su sani ba su kaɗai Allah ya halitta a wannan duniya ba, balle su yi zaton zai bar su sakaka babu wani tsari. Duk halittar da Allah ya yi ya tanadar mata wani tsari da take tafiya a kansa, hatta dabbobi da ya halitta yana gudanar da rayuwarsu ne cikin wani tsari da ya ɗora su a kai. To haka ya zama wajibi rayuwar mutane ta kasance tana gudana ne a kan irin tsarin da Allah ya tanadar musu su gudanar da rayuwa a kansa, wanda shi ne abin da ya aiko annabawansa da shi.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai bayyana mana inda muka yi kama da dabbobi da tsuntsaye ba; ya bar mana abin a buɗe don mu gudanar da tunaninmu mu gano fuskokin kamanceceniyar da kanmu.

9. Babu abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bari bai rubuta shi a cikin Lauhul Mahfuz ba, domin ya umarci Alƙalamin Ƙudura da ya rubuta duk abin da zai faru tun farkon duniya har zuwa tashin alƙiyama. Yarda da haka yana cikin imani da ƙaddara wanda wani rukuni ne daga cikin rukunan imani.

10. Shiriya da ɓata duk suna hannun Allah, don haka ya zama wajibi ga mutum ya riƙa neman shiriya daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

*إِنَّمَا يَسۡتَجِيبُ ٱلَّذِينَ يَسۡمَعُونَۘ وَٱلۡمَوۡتَىٰ يَبۡعَثُهُمُ ٱللَّهُ ثُمَّ إِلَيۡهِ يُرۡجَعُونَ٣٦ وَقَالُواْ لَوۡلَا نُزِّلَ عَلَيۡهِ ءَايَةٞ مِّن رَّبِّهِۦۚ قُلۡ إِنَّ ٱللَّهَ قَادِرٌ عَلَىٰٓ أَن يُنَزِّلَ ءَايَةٗ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ٣٧ وَمَا مِن دَآبَّةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا طَٰٓئِرٖ يَطِيرُ بِجَنَاحَيۡهِ إِلَّآ أُمَمٌ أَمۡثَالُكُمۚ مَّا فَرَّطۡنَا فِي ٱلۡكِتَٰبِ مِن شَيۡءٖۚ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّهِمۡ يُحۡشَرُونَ٣٨ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا صُمّٞ وَبُكۡمٞ فِي ٱلظُّلُمَٰتِۗ مَن يَشَإِ ٱللَّهُ يُضۡلِلۡهُ وَمَن يَشَأۡ يَجۡعَلۡهُ عَلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ٣٩

36. Lalle masu ji su ne kawai suke amsa (kiranka). Matattu kuwa Allah zai tashe su (ranar alƙiyama), sannan zuwa gare Shi za a mayar da su.

37. Kuma suka ce: “Ina ma da an saukar masa da wata aya daga Ubangijinsa ?” Ka ce: “Lalle Allah Mai iko ne a kan Ya saukar da kowace irin aya, sai dai yawancinsu ba sa sanin (haka).”

38. Kuma babu wata dabba da take tafiya a bayan ƙasa, kuma babu wani tsuntsu da yake tashi da fukafukansa, face (su ma) al’ummomi ne irinku. Ba Mu yi sakacin barin wani abu ba a cikin littafi, sannan kuma zuwa ga Ubangijinsu ne za a tara su.

39. Waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu su kurame ne, kuma bebaye ne, suna cikin duffai. Wanda Allah Ya ga dama sai Ya ɓatar da shi, wanda kuwa Ya ga dama sai Ya ɗora shi a kan tafarki madaidaici.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, waɗanda suke amsa kiransa da na Manzonsa su ne kawai masu sauraro da kunnen basira kuma masu fahimta, amma kafirai masu matattun zukata ba a sa ran za su saurare shi, domin su ba su da bambanci da matattu babu abin da suke iya fahimta. Don haka Allah zai fito da su daga ƙaburburansu, ya tattara su a gabansa domin yi musu hisabi a kan ayyukansu.
Har ta kai su waɗannan masu ƙaryata Manzo suna cewa, me ya hana Allah ya saukar wa Annabi (ﷺ) wata mu’ujiza ko aya daga wajensa ba, wadda za ta tabbatar da cewa, shi Manzon Allah ne? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya ba su amsa da cewa: Allah yana da cikakken ikon da zai saukar da kowace irin aya a duk sanda ya ga dama, to amma yana yin komai ne bisa tsari da hikima, sai dai yawancin irin waɗannan mutane ba su san hikimomin Allah a cikin ayyukansa da hukunce-hukuncensa ba, don haka ba abin da suka sani sai jayayya da musu.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani sashe na ayoyinsa a halittarsa, inda ya nuna cewa babu wata dabba da ke tafiya a bayan ƙasa ko wani tsuntsu mai tashi da fukafukansa, face su ma al’ummomi ne kamar mutane. Babu kuma abin da Allah ya bari face sai da ya rubuta shi cikin Lauhul Mahfuzu kuma zuwa gare shi za a tara su gaba ɗayansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, masu ƙaryata ayoyin Alƙur’ani da bayyanannun hujjojin Allah kurame ne, ba sa jin gaskiya, bebaye ne, ba sa iya faɗar gaskiya, kuma suna cikin duhun kafirci, ba sa ganin wani haske a rayuwarsu. Don haka wanda Allah ya yi nufin ɓatar da shi, zai ɓatar da shi, wanda kuma ya yi nufin ya shiryar da shi, to zai ɗora shi a kan miƙaƙken tafarki, don haka shiriya da ɓata duka a hannunsa suke shi kaɗai, yana yin komai bisa hikima.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kowane mutum a asalin halittarsa ya san mahaliccinsa, zuciyarsa ta yi imani da kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da bauta, shi ya sa duk lokacin da kafiri ya shiga wata matsuwa yakan koma ga asalin halittarsa ne, wato (fitrah), sai ya manta duk wani abin bauta ba Allah ba, ya kirawo Allah shi kaɗai.

2. Babu mai yaye cuta da bala'i sai Allah shi kaɗai, don haka duk sa'adda wani abu na damuwa ya same ka, to kada ka kirawo wani ba Allah ba.

3. Talauci da cututtuka da wadata da lafiya, duk abubuwa ne da mutanen kirki suke samun darussa daga gare su, su wa'azantu. Shi ya sa al'amarin mumini duk alheri ne gare shi; idan abin farin ciki ya same shi sai ya gode wa Allah, sai ya zame masa alheri; idan kuwa abin baƙin ciki ne ya same shi sai ya yi haƙuri, sai hakan ya zama alheri a gare shi. Kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa [Muslim #2999].

Amma wanda ba mumini ba idan yana cikin damuwa da matsi, ba zai ɗauki darasi ba ya koma gaba ɗayansa ga Allah, ya bauta masa shi kaɗai. Ko da ya kirawo Allah yana neman taimakonsa, to na wani ɗan lokaci ne; da zarar an yaye masa masifar da yake ciki sai ya sake komawa ga kafircinsa. Idan kuwa ni'ima ce Allah ya nufe shi da ita, to sai ya yi ta ɗagawa da girman kai ga Ubangiji, sai Allah ya yi masa talala har sai lokacin da ya kama shi ba zato ba tsammani a lokacin da ba zai iya kuɓuta ba.

Suratul An'am (40-45)

قُلْ أَرَءَيْتَكُمْ إِنْ أَتَىٰكُمْ عَذَابُ ٱللَّهِ أَوْ أَتَتْكُمُ ٱلسَّاعَةُ أَغَيْرَ ٱللَّهِ تَدْعُونَ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٤٠﴾ بَلْ إِيَّاهُ تَدْعُونَ فَيَكْشِفُ مَا تَدْعُونَ
إِلَيْهِ إِن شَآءَ وَتَنسَوْنَ مَا تُشْرِكُونَ ﴿٤١﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَآ إِلَىٰٓ أُمَمٍ مِّن قَبْلِكَ فَأَخَذْنَٰهُم بِٱلْبَأْسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ لَعَلَّهُمْ يَتَضَرَّعُونَ ﴿٤٢﴾ فَلَوْلَآ إِذْ جَآءَهُم
بَأْسُنَا تَضَرَّعُوا۟ وَلَٰكِن قَسَتْ قُلُوبُهُمْ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٤٣﴾ فَلَمَّا نَسُوا۟ مَا ذُكِّرُوا۟ بِهِۦ فَتَحْنَا عَلَيْهِمْ أَبْوَٰبَ كُلِّ شَىْءٍ
حَتَّىٰٓ إِذَا فَرِحُوا۟ بِمَآ أُوتُوٓا۟ أَخَذْنَٰهُم بَغْتَةً فَإِذَا هُم مُّبْلِسُونَ ﴿٤٤﴾ فَقُطِعَ دَابِرُ ٱلْقَوْمِ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ ۚ وَٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٤٥﴾

40. Ka ce; "Ku ba ni labari, idan da a ce azabar Allah za ta zo muku ko alƙiyama ta zo muku, shin wanin Allah za ku kira, in har kun kasance masu gaskiya?"

41. Ba haka ba ne, (Allah) Shi kaɗai za ku kira, sai Ya yaye abin da kuke roƙonsa a kai idan Ya ga dama, kuma za ku manta abin da kuke haɗa Allah da shi wajen bauta.

42. Kuma lalle Mun aika da (manzanni) zuwa ga al'ummomin da suka gabace ka, sai Muka ɗora musu tsananin talauci da cutuka ko sa ƙasƙantar da kai.

43. To me ya hana lokacin da musibarmu ta zo musu, su ƙasƙantar da kai? Sai dai kuma zukatansu ne suka ƙeƙashe, Shaiɗan kuma ya ƙawata musu abin da suka kasance suna aikatawa.

44. To yayin da suka yi watsi da abin da aka yi musu wa'azi da shi, sai Muka buɗe musu ƙofofin kowane irin abu, har zuwa lokacin da suka yi fariya da abin da aka ba su, sai Muka damƙe su ba zato ba tsammani, sai ga su suna masu yanke ƙauna (daga kowane alheri).

45. Da haka ne aka tumɓuke tushen waɗanda suka yi zalunci. Kuma yabo da kirari sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi Muhammadu (ﷺ) ya tambayi kafirai cewa, idan wata azabar Allah ta afka musu ko ranar alƙiyama ta zo musu, shin za su kira wani ba Allah ba domin ya kuɓutar da su idan har sun kasance masu gaskiya ne wajen bautar wasu alloli ba Allah ba? A'a, ba wanda za su kira sai Allah don ya yaye musu baƙin cikin da ya same su, a wannan lokacin za su manta abubuwan da suke shirka da su sai Allah shi kaɗai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, ya aiko da annabawa kafin Annabi Muhammadu (ﷺ), to amma al'ummominsu sun ƙaryata su, sai Allah ya ɗanɗana musu wata masifa ta tsananin talauci da ƙuncin rayuwa, ya kuma jarrabe su da cututtuka iri-iri, ko watakila sa dawo su ƙasƙantar da kawunansu ga Allah, su bauta masa shi kaɗai.
To amma me ya hana bayan ya jarrabe su da ire-iren waɗannan masifu, su koma gare shi su ƙasƙantar da kansu su bauta masa shi kaɗai? Sai dai kuma zukatansu sun riga sun ƙeƙashe, kuma Shaiɗan ya ƙawata musu miyagun ayyukansu suna ganin su kyawawa, don haka suka ci gaba da kafirci da shirka da saɓon Allah iri-iri.
To lokacin da kafirai suka bar umarnin Allah da gangan, suka yi watsi da wa'azin da ake yi musu na su ji tsoron Allah, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya canza musu yanayin da suke ciki, ya kawo musu wadata maimakon talauci, lafiya madadin cututtuka, ya yi ta yi musu talala har sai da suka saki jiki, suna farin ciki da fariya da ɗagawa saboda ni'imar da suke ciki, sai kawai kwatsam azabar Allah ta zo musu, sai ga su gaba ɗaya sun halaka kamar ba a taɓa yin su ba a bayan ƙasa. Yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai, mai yin yadda ya ga dama.

An karɓo daga Uƙubatu ɗan Amiru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan ka ga Allah yana ba wa bawansa abin da yake so a duniya, tare da yana saɓa masa, to wannan talala ce Allah yake yi masa." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya karanta wannan ayar ta 44. [Ahmad #17311].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ya kamata ga Musulmi ya yi izina da wannan ayar, ya san cewa Allah ya yi masa idanu guda biyu, ya sanya wani sashinsa fari, wani sashin baƙi, ya halicci wani kitse a idanuwansa don kada iska ta busar da su; ruwan idanuwan kuma mai gishiri don kada wannan kitsen ya riƙa wari, kuma ya ba shi hankali wanda yake bambance abubuwa da shi, ya ba shi kunnuwa waɗanda da su yake jin sautuka. Duk waɗannan ni'imomi ya ba shi su ne don ya aikata abin da ya yarda ya aikata da su, kada ya saɓa masa, domin yin haka ya saɓa wa hankali. Kuma lalle ya riƙa tuna ikon Ubangijinsa, wanda idan ya ga dama zai iya ƙwace masa duk waɗannan abubuwa da ya ba shi, ya mayar da shi tamkar wani dutse ko wani itace, ba ya ji, ba ya gani, ba ya fahimtar komai, kuma ba shi da wanda zai dawo masa da su.

2. Samar da mutum cikin irin wannan tsari da waɗannan gaɓoɓi da ya yi masa masu ban mamaki, babban dalili ne a kan samuwar Ubangiji da cancantar a bauta masa shi kaɗai.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko da manzanninsa ne don su riƙa yin albishir ga masu aiki nagari, da gargaɗi ga masu mummunan aiki. Amma bayyana wasu mu'ujizoji wannan ba aikinsu ne ba, aikin Allah ne.

4. Bayanin ni'imar Allah wajen aiko da manzanni ga ɗan'adam, saboda hankalinsa kaɗai ba zai iya ba shi damar sanin abin da Allah yake so da wanda ba ya so ba, ba zai san sunaye da siffofin Allah ba, ba kuma zai iya sanin yadda zai bauta masa ba. Don haka aiko da manzanni buƙata ce ta larura ga ɗan'adam.

5. Ishara zuwa ga hikimar Allah wajen sanya mutane su zama kashi biyu, muminai da kafirai. Domin da babu kafirai, da ba a fahimci ni'imar da ke cikin Musulunci ba.

6. Karyata ayoyin Allah shi yake jawo ukubarsa ga bayi.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cikakken adalin Sarki ne, ba ya azabta bawansa sai ya cancanci a azabtar da shi saboda fasiƙancinsa.

8. An umarci Annabi (ﷺ) da ya bayyana cewa, taskokin Allah ba a hannunsa suke ba, domin kada wani ya ce zai nemi arziƙi a wajensa. Allah ne kaɗai mai bayarwa, mai hanawa, a wurinsa ake nema shi kaɗai.

9. An umarci Annabi da ya bayyana cewa shi bai san gaibu ba; duk abin da yake ba da labarinsa na nan gaba wahayi ne Allah yake yi masa. Don haka furta cewa Annabi ya san gaibu warware ma'anar wannan ayar ne, wanda Musulmi ba zai amince da shi ba.

10. Ya kuma umarce shi da ya bayyana cewa shi ba mala'ika ne ba, don mayar da martani ga masu neman a saukar masa da mala'ika ko a aiko musu da mala'ika maimakon mutum ɗan'uwansu.

11. Shari'a gaba ɗaya daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) take; bai halatta wani ya zo da wata bidi'a da sunan hanyar bautar Allah a karɓa ba.

Suratul An'am (46-50)

قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِنْ أَخَذَ ٱللَّهُ سَمْعَكُمْ وَأَبْصَٰرَكُمْ وَخَتَمَ عَلَىٰ قُلُوبِكُم مَّنْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ يَأْتِيكُم بِهِۦٓ ۗ ٱنظُرْ كَيْفَ نُصَرِّفُ ٱلْءَايَٰتِ ثُمَّ هُمْ يَصْدِفُونَ ﴿٤٦﴾ قُلْ أَرَءَيْتَكُمْ إِنْ أَتَىٰكُمْ عَذَابُ ٱللَّهِ بَغْتَةً أَوْ جَهْرَةً هَلْ يُهْلَكُ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٤٧﴾ وَمَا نُرْسِلُ ٱلْمُرْسَلِينَ إِلَّا مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ ۖ فَمَنْ ءَامَنَ وَأَصْلَحَ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ﴿٤٨﴾ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا يَمَسُّهُمُ ٱلْعَذَابُ بِمَا كَانُوا۟ يَفْسُقُونَ ﴿٤٩﴾ قُل لَّآ أَقُولُ لَكُمْ عِندِى خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ أَعْلَمُ ٱلْغَيْبَ وَلَآ أَقُولُ لَكُمْ إِنِّى مَلَكٌ ۖ إِنْ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَىَّ ۚ قُلْ هَلْ يَسْتَوِى ٱلْأَعْمَىٰ وَٱلْبَصِيرُ ۚ أَفَلَا تَتَفَكَّرُونَ ﴿٥٠﴾

46. Ka ce: "Ku ba ni labari, yanzu idan Allah zai ɗauke jinku da ganinku, kuma Ya ɗora murfi a zukatanku, wane abin bauta ne wanda ba Allah ba, da zai dawo muku da shi?" Duba ka ga yadda Muke sarrafa ayoyi, amma duk da haka suna bijirewa.

47. Ka ce: "Ku ba ni labari, idan da azabar Allah za ta zo muku ba zato ba tsammani ko kuma cikin sani, to shin za a hallakar da (wasu) ba azzaluman mutane ba?"

48. Kuma ba ma aiko da manzanni sai suna masu bushara masu gargaɗi; sannan duk wanda ya yi imani kuma ya kyautata aiki, to babu tsoro a tattare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

49. Waɗanda kuwa suka ƙaryata ayoyinmu, azaba za ta shafe su saboda abin da suka kasance suna yi na fasiƙanci.

50. Ka ce: “Ni ba zan ce da ku a wajena taskokin Allah suke ba, kuma ni ban san gaibu ba, kuma ni ba zan ce da ku ni mala’ika ne ba; ni ba abin da nake bi sai abin da aka yi mini wahayinsa.” Ka ce: “Yanzu makaho da mai gani za su yi daidai? To me ya sa ba za ku yi tunani ba?”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) ya tambayi mushrikai cewa, idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙwace musu jinsu ya mayar da su kurame ko ya ƙwace musu ganinsu ya mayar da su makafi, ya kuma toshe musu zukatansu suka daina fahimtar komai, to shin akwai wani ba Allah ba wanda zai dawo musu da waɗannan abubuwa sai su bauta masa, shi kuma Allah su yi shirka da shi? Allah ya faɗakar da Annabi (ﷺ) da cewa, ya duba ya ga yadda yake koro musu hujjoji, yake bayyana su a fili, amma kuma suna kawar da kawunansu, ba sa dubansu balle su yi aiki da su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa da cewa kafirai su ba shi labari idan har azabar Allah ta zo musu ba shiri ko wani bala’i ya sauka a kansu, shin akwai wanda zai ɗanɗani wannan azabar in ba su azzalumai ba?
Sannan ya ƙara da cewa, bai aiko da manzanni ba sai don su yi albishir da Aljanna ga wanda ya bi Allah, su yi gargaɗi da Wuta ga wanda ya saba wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). To amma duk wanda ya yi imani babu wani tsoro a tare da shi game da abin da yake fuskanta, kuma babu damuwa a kan abin da ya bari a nan duniya. Waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah kuwa, za su gamu da wata azaba saboda kangarewa da kauce wa hanyar Allah da suka yi.
To bayan da kafirai suka matsa wa Manzon Allah (ﷺ) da cewa, sai ya zo musu da wata aya wadda za ta sa su yin imani ko ba sa so, sai Allah ya umarce shi ya faɗa musu cewa, taskokin Allah ba a hannunsa suke ba ballantana ya kawo musu abubuwan da suke nema, kuma shi bai san gaibu ba, kuma bai yi da’awar shi mala’ika ne, mai iya aikata abin da mutane ba za su iya aikatawa ba; shi kawai Manzo ne da Allah ya aiko shi don ya kira mutane zuwa ga bautar Allah shi kaɗai. Duk abin da yake faɗa da abin da yake aikatawa yana yin su ne a bisa wahayin da Allah yake yi masa.
To yanzu za a ce wanda ya bi gaskiya ya miƙa wuya gare ta zai yi daidai da wanda ya saki hanya, ya yi watsi da gaskiya? Ashe yanzu ba za su yi tunani ba su fahimta?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kamalar adalcin Allah. Dubi yadda ya fuskantar da gargaɗi mai ƙarfi zuwa ga Annabi (ﷺ) dangane da batun waɗannan matalautan sahabbai, duk kuwa da kasancewar ya fi su daraja da matsayi a wurin Allah nesa ba kusa ba, to sai dai shi Allah Adalin Sarki ne, wanda yake ba wa kowa haƙƙinsa ba tare da la’akari da matsayinsa ba.

2. Gargaɗi a kan cutar da mutanen kirki, abin da zai kai mutum faɗawa cikin rukunin azzalumai a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Musulunci addini ne na Allah; kowa daga wajensa yake karɓar umarni da hani, don haka kowa a ƙarƙashin tsarinsa da shari’arsa yake. Hatta annabawa ba sa yin gaban kansu wajen bayar da umarni ko hani, dole ne su gudanar da al’amuransu ƙarƙashin dokar Allah.

4. Wajabcin yin gargaɗi da Alƙur’ani, domin babu wa’azin da ya kai shi ratsa jiki da fasahar zance da faɗar gaskiya.

5. Babu mai amfana da wa’azi sai mutumin da yake tsoron ranar lahira.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya jarrabar wani mutum a dalilin wani, sai ya ɓace ya bar hanyar Allah. Misali mutumin da zai ga wani yana aikin alheri da dukiyarsa ko da iliminsa ko da mulkinsa, sai ya

ƙuduri cewa, duk abin da wanen nan yake ciki, ba ruwansa da shi, ko ya ce shi ba zai taɓa amincewa da abin da ya ga wane yana yi ba, sai ya shiga yaƙar wannan aikin na alheri wai saboda ‘wane’ ya riga shi aikata shi, sai wannan ya ɓace a dalilin haka.

7. Lalle wajibi ne masu bin hanyar Allah su gane munin hanyar maƙiyansu don su fahimci gaskiyar da su suke a kai har suke kiran mutane zuwa gare ta, su kuma fahimci cewa su Musulmi ne, kuma masu faɗa da gaskiya maƙiya Allah ne. Wannan shi ne yaƙinin da ya zama wajibi kowane Musulmi ya zama yana da shi a zuciyarsa.

Suratul An’am (51-55)

وَأَنذِرۡ بِهِ ٱلَّذِينَ يَخَافُونَ أَن يُحۡشَرُوٓاْ إِلَىٰ رَبِّهِمۡ لَيۡسَ لَهُم مِّن دُونِهِۦ وَلِيّٞ وَلَا شَفِيعٞ لَّعَلَّهُمۡ يَتَّقُونَ ٥١ وَلَا تَطۡرُدِ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ رَبَّهُم بِٱلۡغَدَوٰةِ وَٱلۡعَشِيِّ يُرِيدُونَ وَجۡهَهُۥۖ مَا عَلَيۡكَ مِنۡ حِسَابِهِم مِّن شَيۡءٖ وَمَا مِنۡ حِسَابِكَ عَلَيۡهِم مِّن شَيۡءٖ فَتَطۡرُدَهُمۡ فَتَكُونَ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥٢ وَكَذَٰلِكَ فَتَنَّا بَعۡضَهُم بِبَعۡضٖ لِّيَقُولُوٓاْ أَهَٰٓؤُلَآءِ مَنَّ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مِّنۢ بَيۡنِنَآۗ أَلَيۡسَ ٱللَّهُ بِأَعۡلَمَ بِٱلشَّٰكِرِينَ ٥٣ وَإِذَا جَآءَكَ ٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِـَٔايَٰتِنَا فَقُلۡ سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمۡۖ كَتَبَ رَبُّكُمۡ عَلَىٰ نَفۡسِهِ ٱلرَّحۡمَةَ أَنَّهُۥ مَنۡ عَمِلَ مِنكُمۡ سُوٓءَۢا بِجَهَٰلَةٖ ثُمَّ تَابَ مِنۢ بَعۡدِهِۦ وَأَصۡلَحَ فَأَنَّهُۥ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٥٤ وَكَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ وَلِتَسۡتَبِينَ سَبِيلُ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٥٥

51. Kuma ka yi gargaɗi da shi (Alƙur’ani) ga waɗanda suke jin tsoron a tattara su a gaban Ubangijinsu, ba su da wani majiɓincin lamari in ba Shi ba, kuma ba su da wani mai ceto, don su kiyaye dokokin Allah.

52. Kuma kada ka kori waɗannan da suke bauta wa Ubangijinsu safe da yamma, suna nufin Fuskarsa (watau suna yi don Shi kaɗai); ba wani abu na haƙƙinsu a kanka, kuma babu wani abu na haƙƙinka a kansu, balle ka kore su, sai ka kasance cikin azzalumai.

53. Kuma kamar haka ne Muka jarrabi sashinsu da sashi, domin su ce: “Yanzu waɗannan su ne Allah Ya yi wa baiwa daga cikinmu?” Ashe Allah ba Shi ne Mafi sanin masu godiya (gare Shi) ba?

54. Kuma idan waɗanda suke yin imani da ayoyinmu sun zo wurinka, to ka ce: *“Sallama a gare ku;”* Ubangijinku Ya wajabta wa kansa yin rahama cewa, lalle cikinku duk wanda ya aikata wani mummunan aiki bisa ga jahilci, sannan daga baya ya tuba kuma ya kyautata aiki, to Shi Mai gafara ne, Mai jin ƙai.”

55. Kuma kamar haka ne Muke rarrabe ayoyi domin tafarkin masu laifuka ya bayyana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) ya yi wa’azi da Alƙur’ani ga mutanen da suke jin tsoron ranar da za a tattara su gaban Ubangijinsu, ba su da wani mai taimakonsu ba Allah ba, kuma ba su da wanda zai cece su daga azabar Allah, ko wataƙila sa yi taƙawa su aikata abin da ake umartar su da shi, su bar abin da ake hana su. Kuma Allah ya yi wa Annabi (ﷺ) kashedi da kada ya kori talakawan sahabbai waɗanda suke bautar Allah safe da yamma, suna masu tsarkake bautarsu ga Allah kawai da neman kusanci da shi.
Dalilin saukar wannan ayar shi ne, abin da Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ruwaito cewa: “Mun kasance mu shida tare da Annabi (ﷺ) sai mushirikai suka ce wa Annabi (ﷺ): ‘Ka kori mutanen nan don kada su riƙa yi mana rashin kunya.’ Sa’ad ya ce: “Na kasance ni ne da Abdullahi ɗan Mas’ud da wani mutum daga ƙabilar Huzailu da Bilalu da wasu mutum huɗu da ba zan tuna sunayensu

ba. To Sai abin da Allah ya ga dama ya auku a zuciyar Manzon Allah (ﷺ) ya auku, watau ya saƙa wani abu a ransa. Sai Allah ya saukar da wannan ayar.” [Muslim #2413].

Wato Manzo Allah (ﷺ) koyaushe yana kwaɗayin musuluntar waɗannan mushirikai, saboda maslahar da take ciki na kasancewarsu shugabanni ne; idan sun musulunta to mabiyansu ma duk za su musulunta, daga lokacin kuma za a daina gallaza wa Musulmi marasa gata, sai ya yi tunanin ya sallami talakawan da suke zuwa majalisarsa don ya samu nasarar farautar waɗancan manyan Kuraishawa, sai Allah ya hana shi aikata hakan, ya faɗa masa cewa, kowa hisabinsa na ga Allah, shi ne zai yi wa kowa sakayya a kan ayyukansa na alheri ko na sharri, don haka ba shi ne mai yi musu hisabi ba, su ma ba su ne masu yi masa hisabi ba ballantana ya kore su daga majalisarsa, kuma har idan ya aikata hakan, to ya zama daga cikin azzalumai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar haka ne yake jarrabar sashin wasu mutane da wani sashi; ya yi wani mai wadata wani kuma matalauci, wani mai daraja wani kuma ba kowa ba. To idan wani matalauci ko mai rauni ya musulunta, ya ba da gaskiya, shi kenan sai hakan ya zamanto fitina ga mai wadata da mai daraja har su riƙa cewa: Waɗannan mutanen su ne za a ce Allah ya yi musu baiwar shiriya mu kuma bai yi mana ba? Kuma da a ce wani abin kirki ne ai da mu ne za mu same shi kafin su. Sai Allah ya mayar musu da martani cewa, shi ne ya fi sanin bayinsa masu gode masa, don haka sai ya yi musu kyautar da bai yi wa waninsu ba komai martabarsa da wadatarsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) cewa, ya yi maraba da muminai masu ba da gaskiya da ayoyinsa duk sa’adda suka zo wurinsa, ya ce musu, amincin Allah ya tabbata a gare su, kuma ya yi musu albishir da samun rahamar Allah wadda ya wajabta wa kansa, kuma ya sanar da su cewa, duk wanda ya yi laifi bisa jahilci sannan daga bisani ya tuba ya gyara aikinsa, to Allah mai yawan gafara ne mai yawan jin ƙai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yana bayanin ayoyinsa ne ɓaro-ɓaro don kowa ya gane, don kuma hanyar masu laifi marasa gaskiya ta fito ƙarara kowa ya fahimce ta don ya nisance ta, a rarrabe tsakanin gaskiya da ɓata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dalilin da ya jawo wa kafirai ɓata shi ne bin soye-soyen zukatansu, don haka duk wanda ya bi su za su ɓatar da shi.

2. Wajibi ne ga duk mai neman gaskiya ya dogara da hujja ba ra’ayin riƙau ba.

3. Annabi (ﷺ) bai mallaki komai ba game da uƙubar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake saukar wa bayinsa, wato ba a hannunsa abin yake ba; yana hannun Allah ne, shi ne yake zartar da abin da ya ga dama.

4. Duk wani ɗan’adam akwai iya inda haƙurinsa yake ƙarewa, sai dai ana umartar sa ne da ya jure abin da yake gani na kangarewa da lalacewa; Allah shi kaɗai ne haƙurinsa ba shi da iyaka, yana yin afuwa da yafiya ga bayinsa masu yi masa laifi a ko da yaushe ba tare da gajiyawa ba.

5. A wannan ayar ta 58, Allah ya tabbatar da cewa, da saukar da azaba a hannun Manzon Allah (ﷺ) take, da tuni an gama magana, ya saukar musu da ita, ta halaka su. Wannan kuma ba ya cin karo da abin da ya tabbata a hadisi cewa, mala’ikan duwatsu ya nemi izinin Manzon Allah (ﷺ) a kan ya niƙe mushirikan Kuraishawa da duwatsun garin Makka, amma Manzon Allah (ﷺ) ya ƙi yarda, har ma ya ce masa: “Ina fatan Allah ya fitar da masu bauta masa daga tsatso-tsatson waɗannan kafirai.” [Bukhari #3231 da Muslim #1795].

Wannan ayar ba ta cin karo da wannan hadisin, domin ayar tana magana ne a kan lokacin da su kafiran ne suke neman a halaka su in an isa, Allah ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, da azabar a hannunsa take, da ya saukar musu ita kamar yadda suke buƙata. Amma shi hadisin ba su ne suka nemi a saukar da azabar ba, mala'ika ne ya nemi hakan, sai Annabi (ﷺ) ya nemi a ƙyale su.

Suratul An'am (56-58)

قُلْ إِنِّي نُهِيتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۚ قُل لَّآ أَتَّبِعُ أَهْوَآءَكُمْ قَدْ ضَلَلْتُ إِذًا وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُهْتَدِينَ ﴿٥٦﴾ قُلْ إِنِّى عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّى وَكَذَّبْتُم بِهِۦ ۚ مَا عِندِى مَا تَسْتَعْجِلُونَ بِهِۦٓ ۚ إِنِ ٱلْحُكْمُ إِلَّا لِلَّهِ ۖ يَقُصُّ ٱلْحَقَّ ۖ وَهُوَ خَيْرُ ٱلْفَٰصِلِينَ ﴿٥٧﴾ قُل لَّوْ أَنَّ عِندِى مَا تَسْتَعْجِلُونَ بِهِۦ لَقُضِىَ ٱلْأَمْرُ بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۗ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٥٨﴾

56. Ka ce: "Lalle ni an hana ni in bauta wa abubuwan da kuke bauta wa ba Allah ba." Ka ce: "Ba zan bi soye-soyen zukatanku ba, (idan har zan bi son zuciyarku), to haƙiƙa na ɓata, kuma da ban zama cikin shiryayyu ba kenan" .

57. Ka ce: "Lalle ni ina kan hujja mai ƙarfi daga Ubangijina, ku kuma kun ƙaryata ta. Abin da kuke so in gaggauto muku da shi, ba a hannuna yake ba. Hukunci yana hannun Allah ne Shi kaɗai; Shi ne Yake bayar da labarin gaskiya, kuma Shi ne Fiyayyen masu rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya)".

58. Ka ce: "Da a ce abin da kuke nema a gaggauto muku da shi a wurina yake, to tabbas da ta faru ta ƙare tsakanina da ku. Kuma Allah Shi ne Mafi sanin su wane ne azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya bayyana wa mushirikai cewa, an hana shi ya bauta wa abin da su suke bauta wa ba Allah ba, kuma shi ba zai bi son zuciyarsu ba, domin idan ya yi hakan, to lalle ya ɓata, kuma ba ya daga cikin shiryayyun mutane.
Haka kuma ya umarce shi ya faɗa musu cewa, shi yana kan wata ƙaƙƙarfar hujja daga Ubangijinsa, yayin da su kuma suka ƙaryata gaskiyar da ya zo musu da ita. Haka kuma azabar da suke neman a gaggauto musu da zuwanta ba a hannunsa take ba. Don haka hukunci gaba ɗaya na Allah ne; idan ya ga dama sai ya gaggauto musu da azabar da suka nema, idan kuma ya ga dama sai ya jinkirta zuwanta gwargwadon yadda hikimarsa ta zartar. Duk kuma abin da yake labartawa a littafinsa, gaskiya ne babu kokwanto a cikinsa, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne fiyayyen wanda yake bayyana mai gaskiya da mai ƙarya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya bayyana musu cewa, da a ce azabar da suke neman a gaggauto musu da ita a hannunsa take, da yanzu an gama magana, abin da suke nema ya auku gare su. To amma abin a hannun Allah yake, shi ya fi sanin azzalumai, ya fi sanin sanda ya dace ya saukar musu da azabarsa, domin yana yin komai ne cikin hikima.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu wanda ya san gaibu sai Allah shi kaɗai.

2. Babu abin da yake ɓoye wa Allah komai ƙanƙantarsa a ko'ina yake, a sama ko a ƙasa, a kowane yanayi, a kowane lokaci, mai rai ko matacce, ɗanye ko busasshe.

3. Duk wanda yake da'awar sanin gaibu ta hanyar duba ko bokanci ko ta hanyar taurari ko bugun ƙasa, to wannan ya kafirce wa wannan ayar, yarda da shi ma kafirci ne.

4. Mala'ikun Allah ma'asumai ne, watau ba sa saɓa wa Allah cikin duk abin da ya umarce su da shi.

5. Cikin mala'ikun Allah akwai waɗanda aikinsu shi ne sa ido a kan ayyukan bayinsa, suna tsaron su ba dare ba rana, suna rubuta ayyukansu kyawawa da munana.

6. Allah shi ne mai karɓar rai na haƙiƙa, kamar yadda ya zo a *Suratuz Zumar*, aya ta 42, kuma yana wakilta mala'ikan mutuwa da zartar da wannan aikin, kamar yadda ya ambata a *Suratus Sajda*, aya ta 11, sannan ya haɗa wannan mala'ikan da wasu mala'iku da za su yi aikin tare, kamar yadda wannan ayar ta 61 ta nuna.

Suratul An'am (59-62)

*وَعِندَهُۥ مَفَاتِحُ ٱلۡغَيۡبِ لَا يَعۡلَمُهَآ إِلَّا هُوَۚ وَيَعۡلَمُ مَا فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِۚ وَمَا تَسۡقُطُ مِن وَرَقَةٍ إِلَّا يَعۡلَمُهَا وَلَا حَبَّةٖ فِي ظُلُمَٰتِ ٱلۡأَرۡضِ وَلَا رَطۡبٖ وَلَا يَابِسٍ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٥٩ وَهُوَ ٱلَّذِي يَتَوَفَّىٰكُم بِٱلَّيۡلِ وَيَعۡلَمُ مَا جَرَحۡتُم بِٱلنَّهَارِ ثُمَّ يَبۡعَثُكُمۡ فِيهِ لِيُقۡضَىٰٓ أَجَلٞ مُّسَمّٗىۖ ثُمَّ إِلَيۡهِ مَرۡجِعُكُمۡ ثُمَّ يُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٦٠ وَهُوَ ٱلۡقَاهِرُ فَوۡقَ عِبَادِهِۦۖ وَيُرۡسِلُ عَلَيۡكُمۡ حَفَظَةً حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَحَدَكُمُ ٱلۡمَوۡتُ تَوَفَّتۡهُ رُسُلُنَا وَهُمۡ لَا يُفَرِّطُونَ ٦١ ثُمَّ رُدُّوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ مَوۡلَىٰهُمُ ٱلۡحَقِّۚ أَلَا لَهُ ٱلۡحُكۡمُ وَهُوَ أَسۡرَعُ ٱلۡحَٰسِبِينَ ٦٢*وَعِندَهُۥ مَفَاتِحُ ٱلۡغَيۡبِ لَا يَعۡلَمُهَآ إِلَّا هُوَۚ وَيَعۡلَمُ مَا فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِۚ وَمَا تَسۡقُطُ مِن وَرَقَةٍ إِلَّا يَعۡلَمُهَا وَلَا حَبَّةٖ فِي ظُلُمَٰتِ ٱلۡأَرۡضِ وَلَا رَطۡبٖ وَلَا يَابِسٍ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٥٩ وَهُوَ ٱلَّذِي يَتَوَفَّىٰكُم بِٱلَّيۡلِ وَيَعۡلَمُ مَا جَرَحۡتُم بِٱلنَّهَارِ ثُمَّ يَبۡعَثُكُمۡ فِيهِ لِيُقۡضَىٰٓ أَجَلٞ مُّسَمّٗىۖ ثُمَّ إِلَيۡهِ مَرۡجِعُكُمۡ ثُمَّ يُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٦٠ وَهُوَ ٱلۡقَاهِرُ فَوۡقَ عِبَادِهِۦۖ وَيُرۡسِلُ عَلَيۡكُمۡ حَفَظَةً حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَحَدَكُمُ ٱلۡمَوۡتُ تَوَفَّتۡهُ رُسُلُنَا وَهُمۡ لَا يُفَرِّطُونَ ٦١ ثُمَّ رُدُّوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ مَوۡلَىٰهُمُ ٱلۡحَقِّۚ أَلَا لَهُ ٱلۡحُكۡمُ وَهُوَ أَسۡرَعُ ٱلۡحَٰسِبِينَ ٦٢

59. "Kuma mabuɗan gaibu a wurinsa suke Shi kaɗai, babu wanda ya san su sai Shi. Kuma Ya san ƙididdigar abin da yake kan tudu da na ruwa. Kuma babu wani ganyen itace da zai faɗo, face sai Ya san da shi, kuma ba wata ƙwaya da take cikin duhun ƙasa, kuma ba wani ɗanyen abu ko busasshe, face (bayaninsa) yana cikin Littafi mabayyani.

60. "Kuma Shi ne Yake karɓar rayukanku da daddare, kuma Ya san abin da kuka aikata da rana, sannan Ya tayar da ku a cikinta (ranar), har zuwa lokacin da zai zartar da wani ajali sananne, sannan zuwa gare Shi ne makomarku take, sannan zai ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa.

61. "Kuma Shi ne wanda Yake da iko a kan bayinsa, kuma Yana aiko muku masu tsaro, har zuwa lokacin da mutuwa za ta zo wa ɗayanku, sai manzanninmu su karɓi ransa, kuma su ba sa yin sakaci.

62. "Sannan sai a mayar da su zuwa ga Allah Majiɓincin lamarinsu na gaskiya. Ku saurara, dukkan hukunci nasa ne, kuma Shi ne Mafi gaggawar masu hisabi."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, shi kaɗai ne yake da taskokin gaibu waɗanda babu wanda ya san su sai shi kaɗai, ya san abin da yake kan tudun ƙasa, ya san na cikin teku,

kuma babu wani ganye da zai faɗo daga itaciyarsa face ya san da shi, hakanan babu wata ƙwaya a cikin duffan ƙasa ko wani abu ɗanye ko ƙeƙasasshe face yana nan a rubuce a cikin Lauhul Mahfuzu.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Mabuɗan gaibu biyar ne, babu wanda ya san su sai Allah. Babu wanda ya san abin da mahaifa take ragewa (na lokaci) sai Allah; babu kuma wanda ya san me zai faru gobe sai Allah; babu wanda ya san yaushe ne ruwan sama zai sauka sai Allah; babu kuma wani rai da ya san inda zai mutu sai Allah; kuma babu wanda ya san lokacin tashin alƙiyama sai Allah.” [Bukhari #7379].

An karɓo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: “Duk wanda ya riya cewa Annabi (ﷺ) yana ba da labarin abin da zai faru gobe, to lalle ya yi wa Allah ƙarya babba, Allah yana cewa: Ka ce: “Waɗanda suke sammai da waɗanda suke ƙasa babu wanda ya san gaibu sai Allah.” [Muslim #177].

Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne kaɗai wanda yake karɓar rayukan halittunsa da daddare lokacin barcinsu, idan ya ga dama sai ya riƙe rayukan waɗanda ya riga ya hukunta musu mutuwa, ya sako waɗanda lokacin mutuwarsu bai yi ba, kamar yadda ya yi bayani a cikin *Suratuz Zumar*, aya ta 42. Kuma yana sane da ayyukan da bayi suka yi da rana. Sannan sai ya tashe su daga barcinsu yayin da gari ya waye, domin ya zartar da ajalin da ya iyakance musu na rayuwarsu, kowa ya cinye lokacinsa na duniya, sannan zuwa ga Allah ne shi kaɗai makomarsu take, shi kuma ne zai labarta musu abin da suka kasance suna aikatawa a rayuwarsu ta duniya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne wanda yake sama da bayinsa, dole kowa ya rusuna masa. Kuma shi ne mai aiko da mala’iku masu tsaron bayinsa, har lokacin da mutuwa za ta zo wa ɗaya daga cikinsu, sai mala’ikun Allah su karɓi ransa ba tare da yin sakaci ba a kan aikinsu, watau ba sa karɓar rai kafin lokacin karɓarsa ya yi, ko su bar shi har ya ƙara a kan lokacinsa.
Sannan bayan mutuwa sai a mayar da su zuwa ga majiɓincinsu na gaskiya, wato Allah, wanda shi kaɗai ne mai yin hukunci tsakaninsu da adalci, kuma mafi gaggawar masu hisabi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafiran farko suna komawa ga Allah ne duk lokacin da suka shiga cikin wani tsanani; idan suna cikin walwala kuwa sai su riƙa bauta wa wasu tare da Allah.

2. Duk wata musifa ko wani baƙin ciki da za su sami bawa, to Allah ne kaɗai wanda zai yaye masa su, ya kuɓutar da shi.

3. Ta ko’ina Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya aiko wa da bayinsa azabarsa, kuma babu mai ikon kuɓutar da kansa, don haka kamata ya yi su ji tsoronsa, su rungumi koyarwarsa domin samun tsira.

4. Rashin jituwa da faɗace-faɗace tsakanin al’umma wani nau’i ne na azabar Allah ga wannan al’ummar, don haka tuba ne kaɗai maganinta.

5. Duk wani abu da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin aukuwarsa, to mai aukuwa ne babu makawa, kawai ana jiran lokacinsa ne.

قُلۡ مَن يُنَجِّيكُم مِّن ظُلُمَٰتِ ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِ تَدۡعُونَهُۥ تَضَرُّعٗا وَخُفۡيَةٗ لَّئِنۡ أَنجَىٰنَا مِنۡ هَٰذِهِۦ لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ٦٣ قُلِ ٱللَّهُ يُنَجِّيكُم
مِّنۡهَا وَمِن كُلِّ كَرۡبٖ ثُمَّ أَنتُمۡ تُشۡرِكُونَ ٦٤ قُلۡ هُوَ ٱلۡقَادِرُ عَلَىٰٓ أَن يَبۡعَثَ عَلَيۡكُمۡ عَذَابٗا مِّن فَوۡقِكُمۡ أَوۡ مِن تَحۡتِ أَرۡجُلِكُمۡ أَوۡ يَلۡبِسَكُمۡ
شِيَعٗا وَيُذِيقَ بَعۡضَكُم بَأۡسَ بَعۡضٍۗ ٱنظُرۡ كَيۡفَ نُصَرِّفُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّهُمۡ يَفۡقَهُونَ ٦٥ وَكَذَّبَ بِهِۦ قَوۡمُكَ وَهُوَ ٱلۡحَقُّۚ قُل لَّسۡتُ عَلَيۡكُم
بِوَكِيلٖ ٦٦ لِّكُلِّ نَبَإٖ مُّسۡتَقَرّٞۚ وَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ٦٧

63. Ka ce: “Wane ne yake tserar da ku daga cikin duffai na tudu da na kogi, kuna roƙon sa a fili da a ɓoye (cewa): “Tabbas, in da zai tserar da mu daga wannan, to lalle za mu kasance cikin masu godiya.”

64. Ka ce: “Allah ne zai tserar da ku daga cikinsa (tsoron), da ma duk wani baƙin ciki, sannan sai ga ku kuna yin shirka.”

65. Ka ce: “Shi ne Mai cikakken ikon Ya aiko muku da azaba ta samanku ko ta ƙarƙashin ƙafafuwanku ko Ya mayar da ku ƙungiyoyi daban-daban, kuma Ya ɗanɗana wa sashinku azabar sashi.” Duba ka ga yadda Muke bayyana ayoyi, don su fahimta.

66. Kuma mutanenka sun ƙaryata shi (Alƙur’ani) alhali shi ne gaskiya. Ka ce: “Ni ba wakili ne a kanku ba.

67. “Kowane labari yana da lokaci ne na musamman. Kuma da sannu za ku sani.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) ya tambayi masu yin shirka suna bauta wa wasu abubuwa ba shi ba, idan wata musifa ta tunkaro su yayin da suke tafiya a cikin duffai a bayan ƙasa ko a cikin teku, wane ne zai kuɓutar da su daga wannan musifar in ba Allah ba? Don haka shi kaɗai suke roƙa suna masu ƙasƙantar da kai, suna sirranta addu’o’insu tare da ɗaukar alƙawarin cewa idan ya kuɓutar da su daga wannan musifa, to lalle za su zama daga cikin masu godiya gare shi. Sai Allah ya bayyana musu cewa, bayan ya kuɓutar da su suna komawa ne ga bautar wasu tare da shi. To sai Allah ya umarci Manzon Allah (ﷺ), ya faɗa musu cewa, Allah ne shi kaɗai yake kuɓutar da su daga duk wata musifa da za su shiga, ya yaye musu duk wani baƙin ciki da zai dame su, to amma duk wannan bai hana su koma suna haɗa shi da wasu wajen bauta ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, yana da ikon ya saukar musu da azabarsa ta samansu, kamar ruwan duwatsu ko iska mai tsanani ko ya sako musu da azabarsa ta ƙarƙashin ƙafafuwansu, kamar girgizar ƙasa ko ambaliyar ruwa, hakanan yana da ikon ya jefa rashin jituwa a tsakaninsu, su yi ta faɗa, suna kashe-kashen junansu ko ya ɗora wasunsu a kan wasu, su yi ta azabtar da su.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da Allah ya saukar da faɗarsa: “Ka ce shi mai iko ne a kan ya aiko muku da azaba ta samanku,” sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Ina neman tsari da fuskarka.” Da ya ce: “Ko ta ƙarƙashin ƙafafuwanku,” sai Annabi ya ce: “Ina neman tsari da fuskarka.” Da ya ce: “Ko kuma ya mayar da ku ƙungiya-ƙungiya, ya kuma ɗanɗana wa wasu uƙubar wasu,” sai ya ce: “Waɗannan biyun sun fi sauƙi.” [Bukhari #7313].

An karɓo daga Saubanu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce; “Lalle Allah ya tattaro min duniya wuri guda, sai na ga gabashinta da yammacinta, kuma mulkin al’ummata sai ya kai har inda

aka tattaro mini, kuma an ba ni dukiya iri biyu, ja da fara, kuma na yi wa al'ummata addu'ar kada Allah ya halakar da su da fari na gaba ɗaya, kuma kada ya ɗora maƙiyansu a kansu su ƙarar da su gaba ɗaya, kuma Ubangijina ya faɗa mini cewa: "Ya Muhammadu, ni idan na yanke wani hukunci, to ba a mayar da shi, kuma ni na ba wa al'ummarka cewa, ba zan halakar da su gaba ɗayansu ta hanyar fari ba, kuma ba zan ɗora maƙiyansu a kansu ba har su ƙarar da su gaba ɗayansu, ko da kuwa za su yi musu taron dangi daga ko'ina a duniya, sai dai su a junansu wani sashi ya riƙa kashe wani sashi, ko wasu daga cikinsu su riƙa kama wasu a matsayin bayi." [Muslim #2889].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya duba ya ga yadda yake sarrafa hujjoji iri-iri, yake bayyana musu gaskiya, ko sa fahimta, su bar aikata shirka da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, Kuraishawa mutanen Annabi (ﷺ) sun ƙaryata Alƙur'ani alhalin shi gaskiya ne, sai ya umarce shi ya ce musu: Shi ba mai tsaron su ba ne; shi kawai mai isar da saƙo ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da su da cewa, duk wani labarin da Allah ya bayar, to akwai lokacin aukuwarsa, wanda ba zai yi jinkirin zuwa ba, kuma ba zai gabaci lokacin ba, kuma ba da daɗewa ba mushirikai za su ga azabar da ake yi musu alƙawarin zuwanta idan lokacinta ya zo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kashedi game da zama cikin masu izgili da addini da hukunce-hukuncensa, domin zama da su ba tare da hana su saɓon da suke yi ba, yana nufin yarda da abin da suke yi, kuma yana ƙara musu ƙarfin gwiwar ci gaba da laifinsu. Don haka duk wani mai aikata laifi, to zama da shi lokacin da yake aikata wannan laifin haramun ne.

2. Annabawa sukan iya mantuwa kamar yadda sauran mutane sukan yi, sai dai mantuwarsu ba ta yin tasiri a kan isar da saƙon da aka aiko su da shi.

3. Shaiɗan yakan haifar wa da bawa mantuwar abin da bai kamata ya manta ba, amma ambaton Allah shi yake maganinsa.

4. Wanda ya yi mantuwa ya aikata abin da aka hana shi aikatawa, Allah ba ya kama shi da laifin mantuwar.

5. Idan wa'azi zai ƙara wa wanda ake yi masa shi fanɗarewa da sharri, to barinsa ya zama dole.

6. Wajibi ne a kan Musulmi ya ƙaurace wa waɗanda suka mayar da addini abin wasa da izgili da tsokanar masu riƙo da addininsu da kiran su da wasu sunaye don cin fuska da wulaƙanci. Irin waɗannan mutane zama da su wata annoba ce, ba ya halatta Musulmi na ƙwarai ya kai kansa cikinta, ya halaka kansa yana sane.

7. Kafirai ba su da masu ceton su a ranar lahira, kuma ba za su iya fansar kawunansu daga azabar Allah ba.

8. Ranar lahira 'yan wuta za su ji matsananciyar ƙishirwa, kuma za a shayar da su tafasasshen ruwa ne wanda zai ƙara musu ƙuna a kan ƙunarsu.

Suratul An’am (68-70)

وَإِذَا رَأَيْتَ ٱلَّذِينَ يَخُوضُونَ فِيٓ ءَايَٰتِنَا فَأَعْرِضْ عَنْهُمْ حَتَّىٰ يَخُوضُواْ فِي حَدِيثٍ غَيْرِهِۦۚ وَإِمَّا يُنسِيَنَّكَ ٱلشَّيْطَٰنُ فَلَا تَقْعُدْ بَعْدَ ٱلذِّكْرَىٰ مَعَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٦٨﴾ وَمَا عَلَى ٱلَّذِينَ يَتَّقُونَ مِنْ حِسَابِهِم مِّن شَيْءٍ وَلَٰكِن ذِكْرَىٰ لَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ﴿٦٩﴾ وَذَرِ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ دِينَهُمْ لَعِبًا وَلَهْوًا وَغَرَّتْهُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَاۚ وَذَكِّرْ بِهِۦٓ أَن تُبْسَلَ نَفْسٌۢ بِمَا كَسَبَتْ لَيْسَ لَهَا مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلِيٌّ وَلَا شَفِيعٌ وَإِن تَعْدِلْ كُلَّ عَدْلٍ لَّا يُؤْخَذْ مِنْهَآۗ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ أُبْسِلُواْ بِمَا كَسَبُواْۖ لَهُمْ شَرَابٌ مِّنْ حَمِيمٍ وَعَذَابٌ أَلِيمٌۢ بِمَا كَانُواْ يَكْفُرُونَ ﴿٧٠﴾

68. Kuma idan ka ga waɗanda suke kutsawa cikin ayoyinmu (suna izgili), to ka rabu da su, har sai sun canja wani zancen da ba wancan ba. Amma in da Shaiɗan zai mantar da kai kuwa, to bayan ka tuna kar ka sake zama tare da azzalumai.

69. Kuma babu wani laifi a kan waɗanda suke tsoron haɗuwarsu da Allah (don sun zauna da su), sai dai kuma (dole su yi) musu wa’azi don su tsorata.

70. Ka rabu da waɗanda suka ɗauki addininsu wasa da sharholiya, rayuwarsu ta duniya kuma ta ruɗe su. Ka kuma yi gargaɗi da shi (Alƙur’ani), saboda kada a jarrabi rai da abin da ya aikata wanda ba ya da wani mataimaki ko mai ceto ban da Allah, ko da kuwa (ran) ya ba da kowace irin fansa ba za a karɓa ba daga gare shi. Waɗancan su ne waɗanda aka kange (don yi musu azaba) saboda abin da suka aikata; suna da abin sha na tafasasshen ruwa da kuma azaba mai raɗaɗi saboda abin da suka zamanto suna kafircewa (da shi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya kawar da kansa daga masu yin izgili da ayoyin Allah suna ƙaryata su, idan ya gansu suna irin wannan aiki, to kada ya zauna a majalisarsu har sai sun daina abin da suke yi ɗin nan, sun shiga wata hirar daban. To amma lokacin da Shaiɗan ya mantar da shi har ya zauna cikinsu, sannan daga bisani ya tuna, to ya yi maza-maza ya tashi daga wannan majalisa, kada ya ci gaba da zama tare da azzalumai bayan ya tuna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin cewa, idan muminai masu tsoron Allah suka guje wa masu izgili da ayoyin Allah, to babu wani laifi a kansu, amma kuma wajibi ne a kansu su ci gaba da yi musu wa’azi ko sa ji tsoron Allah su bar kafirci.l
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya rabu da mutanen da suka mayar da addinin Allah abin wasa da izgili suna ƙaryata ayoyin Allah, ya umarce shi da ya yi musu wa’azi da Alƙur’ani don su yi imani su bi gaskiya, don kada a tsare wani rai saboda zunubin da ya yi, ya rasa samun tsira duniya da lahira, ya faɗa halaka da azabar Allah a lokacin da babu mai kuɓutar da shi daga gareta, kuma ba mai ceton da zai nema masa afuwa a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Kuma wannan rai duk abin da zai bayar domin ya fanshi kansa daga azabar Allah, ba za a karɓa ba. To waɗannan mutane su ne waɗanda aka riga aka danƙa su ga azabar Allah, wadda ba su da wata mafita daga cikinta, saboda irin ayyukan laifi da suka tafka a duniya, kuma suna da abin sha mai tsananin zafi da wata azaba mai raɗaɗi sakamakon kafircinsu a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1.Shiriyar Allah ita ce kaɗai shiriya, duk sa’adda mutum ya bar ta, to ya kama hanyar ɓata ne da halaka.

2. Allah shi kaɗai ne ya cancanci a bauta masa, shi ne mai amfanarwa mai cutarwa, kuma babu mai iya yin haka sai shi.

3. Wanda duk ya saki Musulunci ya kama shirka ko ɓata, to ya zama kamar mutumin da shaiɗanun aljanu suka ɗauke shi suka tafi da shi suka jefar da shi a ƙungurmin daji. Wannan kuwa lalle ya yi nisan da ba zai taɓa jin kiran mai kiransa ba balle ya gane hanyar dawowa daga wannan dajin da yake ciki ba.

4. Allah shi ne mai cikakken mulki mai ɗorewa har abada.

5. Shi kaɗai ne masanin gaibu, babu wanda ya san gaibu sai shi.

Suratul An'am (71-73)

قُلْ أَنَدْعُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُنَا وَلَا يَضُرُّنَا وَنُرَدُّ عَلَىٰٓ أَعْقَابِنَا بَعْدَ إِذْ هَدَىٰنَا ٱللَّهُ كَٱلَّذِى ٱسْتَهْوَتْهُ ٱلشَّيَٰطِينُ فِى ٱلْأَرْضِ حَيْرَانَ لَهُۥٓ أَصْحَٰبٌ يَدْعُونَهُۥٓ إِلَى ٱلْهُدَى ٱئْتِنَا ۗ قُلْ إِنَّ هُدَى ٱللَّهِ هُوَ ٱلْهُدَىٰ ۖ وَأُمِرْنَا لِنُسْلِمَ لِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٧١﴾ وَأَنْ أَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَٱتَّقُوهُ ۚ وَهُوَ ٱلَّذِىٓ إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿٧٢﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ ۖ وَيَوْمَ يَقُولُ كُن فَيَكُونُ ۚ قَوْلُهُ ٱلْحَقُّ ۚ وَلَهُ ٱلْمُلْكُ يَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ ۚ عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ ﴿٧٣﴾

71. Ka ce: "Shin yanzu ma riƙa bauta wa wani wanda ba Allah ba, abin da ba zai amfane mu ba, kuma ba zai cutar da mu ba, mu koma gidan jiya (kafirai) bayan kuwa Allah Ya shiryar da mu, (mu koma) kamar wanda shaiɗanu suka ɓatar da shi yana ta ɗimuwa a bayan ƙasa, ga shi da wasu abokai suna kiran sa zuwa ga shiriya, (suna cewa): "Ka zo (mu bi tafarkin shiriya)." Ka ce: "Lalle shiriyar Allah fa ita kaɗai ce shiriya; kuma mu an umarce mu da mu miƙa wuya ne kaɗai ga Ubangijin talikai.

72. "Kuma ku tsayar da salla kuma ku kiyaye dokokinsa. Kuma Shi ne Wanda za a tara ku zuwa gare Shi.

73. "Kuma Shi ne Wanda ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya; kuma (ku tuna) ranar da zai ce da abu: 'Kasance!' Nan take sai ya kasance. Maganarsa gaskiya ce. Kuma Shi ne Yake da cikakken mulki a ranar da za a busa ƙaho Masanin gaibu da sarari, kuma Shi ne Mai hikima, Mai cikakken sani."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa mushirikai cewa, yanzu ta yaya ma za mu bauta wa wasu abubuwa ba Allah ba, waɗanda ba za su amfane mu da komai ba komai ƙanƙantarsa, hakanan ba za su iya cutar da mu da komai ba don mun saɓa musu? Haka kawai mu koma cikin ɓata da kafirci bayan Allah ya riga ya shiryar da mu zuwa ga Musulunci, mu zama kamar mutumin da shaiɗanu suka kautar da shi daga kan hanyarsa, alhalin abokansa suna ta kiran sa ya dawo kan hanya wadda ita ce za ta kai shi wajen buƙatarsa, suna ta roƙon sa da ya biyo su don su haɗu tare da shi a kan shiriya? Sai aka umarci Manzon Allah ya faɗa musu cewa, shiriyar Allah ita ce shiriya ta gaskiya, kuma an umarce mu mu miƙa wuyanmu ga Allah, mu sallama wa shiriyarsa, kuma mu tsayar da salla, kuma mu ji tsoron sa ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da shi da barin abin da ya hana, domin a gabansa za a tara kowa da kowa ranar alƙiyama, ya saka wa kowa da irin aikin da ya yi na alheri ko sharri.
Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mahaliccin sammai da ƙasa da ranar lahira wadda za ta tsaya da faɗarsa: 'Kasance', sai ta kasance tamkar ƙiftawar ido ko fiye da haka. Maganarsa kuma gaskiya ce, babu kokwanto cikinta, kuma shi ne wanda ya kaɗaita da mulki a wannan ranar, babu mai ja da shi, shi ne masanin abin da ke ɓoye da wanda yake a fili, babu abin da yake ɓuya daga gare shi, kuma gwani ne mai cikakkiyar hikima da yake ajiye komai a muhallinsa da ya dace, masanin komai, cikinsa da wajensa; ya san duk ayyukan bayinsa, don haka zai yi wa kowa sakamako gwargwadon aikinsa na alheri ko na sharri.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Na ƙasa ya yi wa na sama da shi nasiha ta hanyar da ta dace ba ya nufin rashin biyayya.

2. Bayyana wa wanda yake cikin ɓata cewa shi ɓatacce ne, ba ya nufin cin fuska ko wulaƙanci, ko da kuwa ga wanda aka umarci mutum ne ya girmama shi.

3. Yi wa masu aikata laifi nasiha cikin hikima hanya ce irin ta annabawan Allah da ya wajaba ga kowane mai kira zuwa ga Allah ya bi.

4. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai taɓa yin shirka da Allah ba, kamar yadda ayoyi da dama suka ambata. Kiran tauraro da wata da rana ubangijinsa ba yana nufin ya yarda da hakan ba ne; ya yi haka ne domin jan hankalin mutanensa su fahimci mummunar aƙidar da suke kai.

5. Shiriya ta Allah ce shi kaɗai, yana shiryar da wanda ya ga dama, shi ya sa ya umarce mu mu roƙi shiriyarsa a cikin sallolinmu a kullum.

6. Addinin Allah shi ne bijire wa duk wani abin bauta ba Allah ba tare da ɓauta wa Allah shi kaɗai, wannan kuma shi ne ma’anar Kalmar Shahada da muke faɗa.7. Annabi Ibrahimu shi ne jagoran masu kaiɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul An’am (74-79)

*وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ ءَازَرَ أَتَتَّخِذُ أَصْنَامًا ءَالِهَةً إِنِّيٓ أَرَىٰكَ وَقَوْمَكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ﴿٧٤﴾ وَكَذَٰلِكَ نُرِيٓ إِبْرَٰهِيمَ مَلَكُوتَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ وَلِيَكُونَ مِنَ ٱلْمُوقِنِينَ ﴿٧٥﴾ فَلَمَّا جَنَّ عَلَيْهِ ٱلَّيْلُ رَءَا كَوْكَبًا ۖ قَالَ هَٰذَا رَبِّي ۖ فَلَمَّآ أَفَلَ قَالَ لَآ أُحِبُّ ٱلْءَافِلِينَ ﴿٧٦﴾ فَلَمَّا رَءَا ٱلْقَمَرَ بَازِغًا
قَالَ هَٰذَا رَبِّي ۖ فَلَمَّآ أَفَلَ قَالَ لَئِن لَّمْ يَهْدِنِي رَبِّي لَأَكُونَنَّ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلضَّآلِّينَ ﴿٧٧﴾ فَلَمَّا رَءَا ٱلشَّمْسَ بَازِغَةً قَالَ هَٰذَا رَبِّي هَٰذَآ أَكْبَرُ ۖ فَلَمَّآ
أَفَلَتْ قَالَ يَٰقَوْمِ إِنِّي بَرِيٓءٞ مِّمَّا تُشْرِكُونَ ﴿٧٨﴾ إِنِّي وَجَّهْتُ وَجْهِيَ لِلَّذِي فَطَرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ حَنِيفًا ۖ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٧٩﴾

74. Kuma (ka tuna) lokacin da Ibrahimu ya ce da babansa Azaru: “Yanzu ka riƙi gumaka a matsayin alloli? Lalle ni ina ganin ka kai da mutanenka, kuna cikin ɓata mabayyani.”

75. Kuma kamar haka ne Muke nuna wa Ibrahimu halittun sammai da ƙasa, domin ya kasance cikin masu sakankancewa.

76. To yayin da dare ya lulluɓe shi, ya ga tauraro, sai ya ce; “Wannan shi ne ubangijina;” sannan yayin da ya ɓace, sai ya ce: “Ni fa ba na son abubuwa masu gushewa.”

77. Sa’annan yayin da ya ga wata ya fito, sai ya ce; “Wannan shi ne ubangijina;” sannan yayin da ya gushe, sai ya ce: “Lalle idan Ubangijina bai shiryar da ni ba, haƙiƙa zan kasance daga cikin mutane ɓatattu.”

78. Sannan yayin da ya ga rana ta hudo, sai ya ce: “Wannan shi ne ubangijina, wannan shi ya fi girma;” sannan yayin da ta ɓace, sai ya ce: “Ya ku mutanena, haƙiƙa ni ba ruwana da abin da kuke haɗa Allah da shi.

79. “Lalle ni kam na juyar da fuskata ga Wanda Ya halicci sammai da ƙasa, ina mai kauce wa ɓarna kuma ni ba na cikin masu yin shirka.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba mu labarin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa masu bauta wa taurari da rana da wata, cikinsu har da mahaifinsa mai suna Azaru. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya koya wa Annabi Ibrahimu hanyar da zai yi wa mutanensa wa’azi cikin hikima da lalama don ya ja hankalinsu har su fahimci abin da suka ɗauka shi ne Ubangiji suna bautarsa ba haka abin yake ba. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fara wa’azinsa ta kan mahaifinsa, yayin da ya ce masa: “Yanzu ka riƙa bauta wa gumaka ba Allah ba? Ni ina ganin ka kai da mutanenka masu bautar gumaka kuna cikin ɓata mabayyani.” Don haka sai Allah ya nuna wa Annabi Ibrahimu hallittun da sama ta ƙunsa masu nuna girman mulkinsa don ya kafa wa mutanensa hujja da su a kan kaɗaita Allah da bauta, kuma ya zama cikin masu tabbaci a kan Tauhidi da yaƙini a kan hakan.
To lokacin da dare ya rufe da duhunsa, taurari suka fito, sai Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fito cikin mutanensa ya ce musu: “Wannan ne ubangijina.” Bayan tauraro ya ɓace an daina ganin sa, sai ya ce musu: “Ni kuma ba na son abin bauta mai gushewa ya ɓace wa wanda yake bauta masa.” Don hakan yana nuna ba zai samu biyan buƙatarsa a wajensa ba. To sai kuma ya ga wata ya fito, sai ya ce musu: “Wannan shi ne ubangijina.” Bayan ya ɓace an daina ganin sa, sai Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ce, idan dai ba Allah ne ya shiryar da shi ba, to tabbas zai zama daga cikin waɗannan ɓatattun mutanen. To yayin kuma da ya ga rana ta fito sai ya ce: “To wannan kam shi ne ubangijina, domin ya fi sauran girma.” To bayan rana ta faɗi an daina ganin ta, sai ya ce: “To ni dai daga yanzu ba ruwana da duk abin da kuke bauta wa wanda ba Allah ba; ni na juyar da fuskata ga Allah shi kaɗai, wanda shi ne ya ƙagi halittar sammai da ƙasa ba tare da ya kwaikwayi wani ba; ba ni ba hanyar shirka, ina tsaye ƙyam a kan Tauhidi, kuma ba zan taɓa zama cikin masu shirka ba.”

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutanen Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba su yi imani da shi ba, duk kuwa da ƙarfin hujjar da ya nuna musu wadda hankali zai iya saurin risker ta ba tare da wata wahala ba. Wannan ya nuna cewa, ƙarfin hujjar mai gaskiya da hikimar wa’azinsa ba shi ne zai sa mutane su gaskata shi, su bi shi ba; ita shiriya ai dace ne daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Duk wanda ba shi da abin da zai sa a ji tsoron sa, ya tabbata shi marar iko ne a kan komai, wanda kuma ba shi da ikon komai ba zai taɓa zama abin bauta ba. Allah shi ne wanda yake da ikon amfanarwa da cutarwa, don haka shi ya wajaba a ji tsoron sa, a kuma bauta masa shi kaɗai.

3. Ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yalwaci kowa da komai.

4. Abin da kafirai suka nuna na rashin tsoronsu ga Allah ya fi zama abin mamaki fiye da rashin tsoron Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ga gumakansu. Wannan yana nuna cewa, sun san Allah, sai dai kawai suna haɗa gumakansu da shi ne wajen bauta, shi ya sa ya kafa musu hujja da cewa, suna bauta wa abin da Allah bai saukar musu da wata hujja a kan bautarsa ba.

5. Mafi girman zalunci shi ne shirka da Allah.

6. Babu mai samun aminci a wurin Allah sai wanda ya guji yi wa Allah shirka. Aminci yana nufin samun kuɓuta daga duk wani abin tsoro da tsira daga azaba da tsiyacewa. Waɗanda ba su haɗa imaninsu da kowanne irin zalunci na shirka ko saɓon Allah ba, waɗannan su za su samu cikakken aminci da cikakkiyar

shiriya. Waɗanda kuwa ba su haɗa imaninsu da shirka ne kawai ba, amma sun aikata ayyukan saɓon Allah, to za su samu asalin amincin da kuma asalin shiriyar, amma ba cikakku ba.

7. Wanda Allah ya sanar da shi hujjojin da yake iya tabbatar wa da abokan husuma kaɗaitakar Allah, kuma yake rushe duk wata rikitacciyar aƙida, to wannan Allah zai ɗaukaka darajojinsa yadda ya ga dama.

Suratul An'am (80-83)

وَحَآجَّهُۥ قَوۡمُهُۥۚ قَالَ أَتُحَٰٓجُّوٓنِّي فِي ٱللَّهِ وَقَدۡ هَدَىٰنِۚ وَلَآ أَخَافُ مَا تُشۡرِكُونَ بِهِۦٓ إِلَّآ أَن يَشَآءَ رَبِّي شَيۡـٔٗاۗ وَسِعَ رَبِّي كُلَّ شَيۡءٍ عِلۡمًاۗ أَفَلَا تَتَذَكَّرُونَ ٨٠ وَكَيۡفَ أَخَافُ مَآ أَشۡرَكۡتُمۡ وَلَا تَخَافُونَ أَنَّكُمۡ أَشۡرَكۡتُم بِٱللَّهِ مَا لَمۡ يُنَزِّلۡ بِهِۦ عَلَيۡكُمۡ سُلۡطَٰنٗاۚ فَأَيُّ ٱلۡفَرِيقَيۡنِ أَحَقُّ بِٱلۡأَمۡنِۖ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٨١ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمۡ يَلۡبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلۡمٍ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلۡأَمۡنُ وَهُم مُّهۡتَدُونَ ٨٢ وَتِلۡكَ حُجَّتُنَآ ءَاتَيۡنَٰهَآ إِبۡرَٰهِيمَ عَلَىٰ قَوۡمِهِۦۚ نَرۡفَعُ دَرَجَٰتٖ مَّن نَّشَآءُۗ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٞ ٨٣

80. Kuma mutanensa sun yi jayayya da shi; (sai) ya ce: "Shin yanzu kwa riƙa jayayya da ni game da (kaɗaitakar) Allah, alhalin kuwa Ya shiryar da ni? Kuma ba na jin tsoron abin da kuke sanya wa Allah kishiya da shi, sai abin da Ubangijina Ya ga dama. Kuma ilimin Ubangijina ya yalwaci komai. Shin ba za ku wa'azantu ba?

81. "To ta ƙaƙa kuwa zan ji tsoron abin da kuka tara da (Allah), alhali ku kuma ba kwa jin tsoron kun sanya wa Allah kishiya, abin da kuwa bai saukar muku da wata hujja a kai ba? To wane ɓangare ne cikin ɓangarori biyu, ya fi dacewa da samun aminci; in har kun kasance kun sani?

82. "Waɗanda suka yi imani, kuma ba su garwaya imaninsu da zalunci ba, waɗannan su suke da aminci, kuma su ne shiryayyu."

83. Kuma waɗancan su ne hujjojinmu da Muka ba wa Ibrahimu su a kan mutanensa. Muna ɗaukaka darajojin waɗanda Muka ga dama. Lalle Ubangijinka Mai hikima ne, Mai yawan sani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana nuna mana cewa, bayan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gama nuna wa mutanensa hujjoji na ƙuru-ƙuru, masu tabbatar da lalacewar bautar gumaka da taurari da wata da rana ba Allah ba, sai mutanensa suka bijire, suka shiga jayayya da shi game da bayanin Tauhidin Allah da wajabcin guje wa bautar gumaka, da cewa, yanzu ta yaya za su riƙa jayayya da shi a kan kaɗaita Allah, alhali ya nuna masa hanyar gaskiya kuma ya bi? To sai ya tabbatar musu cewa shi ba ya jin tsoron gumakansu da suke bauta wa ba Allah ba, domin ya san ba sa amfanarwa ba sa kuma cutarwa. Don haka ba su isa su yi masa komai ba, sai abin da Ubangijinsa ya ga dama ya same shi; ilimin Ubangijinsa kuma ya kewaye komai. To yanzu ba za su wa'azantu ba? Kuma ma ta yaya shi zai ji tsoron gumakan da suke haɗawa da Allah wajen bauta, alhali su ba sa jin tsoron yi wa Allah shirka da abin da bai saukar musu wata hujja a kansa ba, kuma ya yi imani Allah shi ne mai iko a kan komai? To sai aka yi tambaya cewa cikin ƙungiyoyin nan guda biyu wane ne ya fi cancanta ya samu aminci? Wanda ya kaɗaita Allah da bauta, ko kuma wanda ya yi shirka da Allah? Ai sai su ba da amsa idan sun kasance sun sani.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa tambayar Annabi Ibrahimu wadda take a fili da cewa: "Waɗanda suka yi imani, kuma ba su cuɗanya imaninsu da shirka ba, to waɗannan su ne masu aminci, kuma su ne shiryayyu."

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'udu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da faɗar Allah ta sauka mai cewa: "Waɗanda suka yi imani…" har zuwa ƙarshe sai wannan ya damu sahabban Annabi (ﷺ), suka ce: "Wane ne a cikinmu bai zalunci kansa ba?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Abin ba kamar yadda kuke zato ba ne; al'amarin ai kamar yadda Lukumanu ne yake faɗa wa ɗansa cewa: 'Ya kai ɗana, kada ka yi shirka da Allah, lalle shirka zalunci ne mai girma.' [Bukhari #6933, da Muslim #124].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan hujjarsa ce wadda ya bai wa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a kan mutanensa, kuma shi Allah yana ɗaukaka darajar wanda ya ga dama ne. Lalle kuma shi mai hikima ne, kuma mai cikakken sani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi sakayya ga Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya ba shi zuriya ta ƙwarai lokacin da ya rabu da mutanensa da 'yan'uwansa ya yi hijira don ya bauta wa Allah shi kaɗai. Don haka duk wanda zai rabu da danginsa da mutanensa saboda Allah, to tabbas Allah zai ba shi waɗanda za su faranta masa rai a cikin zurriyarsa.

2. Yana daga cikin cikar farin cikin uba, Allah ya ba shi ɗa nagari.

3. Wanda ya kyautata aikinsa, Allah zai ƙara masa shiriya.

4. Darajar annabawa a wurin Allah ta fi ta waliyyai.

5. Dangantaka ita kaɗai ba ta zamowa sanadiyyar zaɓi a wurin Allah;, Allah yana zaɓar waɗanda ya ga dama ne a cikin bayinsa, ya shiryar da su tafarki madaidaici.

6. Tsoratarwa game da shirka. Da a ce waɗannan zaɓaɓɓu cikin bayin Allah za su yi shirka, su bar Tauhidi, to da makomarsu ita ce lalacewar kyawawan ayyukansu da suka yi a baya.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai taimaki addininsa da ya aiko Annabinsa Muhammadu (ﷺ) da shi komai ƙiyayyar maƙiya da makircinsu.

8. Tabbatar da gamewar saƙon Annabi (ﷺ) ga duniya baki ɗaya.

Suratul An'am (84-90)

وَوَهَبۡنَا لَهُۥٓ إِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَۚ كُلّٗا هَدَيۡنَاۚ وَنُوحٗا هَدَيۡنَا مِن قَبۡلُۖ وَمِن ذُرِّيَّتِهِۦ دَاوُۥدَ وَسُلَيۡمَٰنَ وَأَيُّوبَ وَيُوسُفَ وَمُوسَىٰ وَهَٰرُونَۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٨٤ وَزَكَرِيَّا وَيَحۡيَىٰ وَعِيسَىٰ وَإِلۡيَاسَۖ كُلّٞ مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٨٥ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَٱلۡيَسَعَ وَيُونُسَ وَلُوطٗاۚ وَكُلّٗا فَضَّلۡنَا عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ٨٦ وَمِنۡ ءَابَآئِهِمۡ وَذُرِّيَّٰتِهِمۡ وَإِخۡوَٰنِهِمۡۖ وَٱجۡتَبَيۡنَٰهُمۡ وَهَدَيۡنَٰهُمۡ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٨٧ ذَٰلِكَ هُدَى ٱللَّهِ يَهۡدِي بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۚ وَلَوۡ أَشۡرَكُواْ لَحَبِطَ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٨٨ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحُكۡمَ وَٱلنُّبُوَّةَۚ فَإِن يَكۡفُرۡ بِهَا هَٰٓؤُلَآءِ فَقَدۡ وَكَّلۡنَا بِهَا قَوۡمٗا لَّيۡسُواْ بِهَا بِكَٰفِرِينَ ٨٩ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ هَدَى ٱللَّهُۖ فَبِهُدَىٰهُمُ ٱقۡتَدِهۡۗ قُل لَّآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ أَجۡرًاۖ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرَىٰ لِلۡعَٰلَمِينَ ٩٠

84. Kuma Muka ba shi Ishaƙa da Ya'aƙubu. Kowanne daga cikinsu Mun shiryar da shi, kuma Mun shiryar da Nuhu tun gabaninsu. Kuma daga cikin zurriyarsa akwai Dawudu da Sulaimanu da Ayyuba da Yusufu da Musa da Haruna. Kuma kamar haka ne Muke saka wa masu kyautata (ayyukansu).

85. Da Zakariyya da Yahaya da Isa da Iliyasu; kowanne daga cikinsu yana cikin salihan bayi.

86. Da Isma'ilu da Alyasa'u da Yunusu da Luɗu. Kowanne daga cikinsu kuma Mun fifita shi a kan (sauran) talikai.

87. Kuma daga cikin iyayensu da zurriyarsu da 'yan'uwansu; duka Mun zaɓe su, kuma Mun shiryar da su zuwa ga tafarki madaidaici.

88. Wannan ita ce shiriyar Allah wadda da ita ne Yake shiryar da wanda Ya ga dama cikin bayinsa. Kuma da a ce sun yi shirka, to lalle da duk abin da suka kasance suna aikatawa ya rushe.

89. Waɗannan su ne waɗanda Muka bai wa littattafai da hukunci da annabta. To idan waɗancan (mutanen Makka) suka kafirce mata (shiriya), to haƙiƙa Mun shirya musu waɗansu mutane waɗanda ba za su kafirce mata ba.

90. Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya shiryar; don haka ka yi koyi da irin shiriyarsu. Ka ce: "Ba na roƙon ku wani lada game da shi (Alƙur'ani); shi ba komai ba ne face tunatarwa ga talikai."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin baiwar da ya yi wa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ta zuriyya ta ƙwarai, ya zaɓi annabawa da yawa daga cikinsu. Wannan daraja ce da babu irinta. Allah ya yi masa kyautar ɗansa Annabi Ishaƙa da jikansa Annabi Ya'aƙubu ɗan Is'haƙu, ya kuma shiryar da su gaba ɗaya zuwa ga miƙaƙƙen tafarki. Kuma Allah ya shiryar da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) tun gabanin Annabi Ibrahimu da ɗansa Annabi Ishaƙa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da jikansa Annabi Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Daga cikin zuriyyar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuma akwai Annabi Dawudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Sulaimanu ɗan Dawudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Ayyuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ɗan'uwansa Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). To kamar yadda Allah ya datar da waɗannan manzanni, suka zama masu bin hanyar gaskiya, to hakanan yake kyautata sakamakonsa ga duk wanda ya kyautata aikinsa, shi ma zai datar da shi ya kama hanyar gaskiya, kuma ya samu zuriya ta ƙwarai masu yi masa addu'a a bayansa.

Hakanan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiryar da Annabi Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Yahaya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Ilyasu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi); dukansu suna cikin mutanen kirki.

Hakanan ya shiryar da Annabi Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Al-Yasa'u (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya fifita darajar waɗannan annabawa a zamunansu.

Har ila yau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiryar da sashin iyayen annabawan can da aka ambata, ya shiryar da wasu daga cikin zurriyyarsu da wasu 'yan'uwansu, ya zaɓe su ya ɗora su akan miƙaƙƙiyar hanya.

To wannan shiriyar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa waɗannan annabawa da zurriyarsu, ita ce shiriyar da babu irinta; da ita yake shiryar da wanda ya ga dama daga bayinsa. Duk da haka waɗannan annabawan da a ce sun aikata shirka, to da duk ayyukansu na alheri sun rushe, ba za su amfane su da komai ba.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan annabawa ya saukar musu da littattafai, ya sanar da su hukunce-hukuncen da suka ƙunsa, sun kuma isar da saƙonsa. To da a ce kafiran Kuraishawa da sauran kafiran duniya sun bijire wa Annabi da Alƙur'anin da Allah ya saukar masa, to lalle Allah ya tanadar masa wasu mutane waɗanda ba za su kafirce masa ba, su ne sahabbansa da sauran muminai har zuwa tashin alƙiyama.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yaba wa waɗannan annabawan da manzanni cewa su ne waɗanda ya shiryar da su suka riƙe addini na gaskiya, suka yi aiki da shi. Don haka sai ya umarci Annabinsa (ﷺ) da ya yi koyi da shiriyarsu, kuma ya faɗa wa mushrikai cewa, ba ya neman su biya shi wani lada a kan isar musu da saƙon Allah da yake yi; wannan aiki nasa kuma ba wani abu ne ba wanda ya wuce wa'azi ga talikai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya musanta shari'ar Allah da umarninsa da haninsa, ya mayar da mutane kamar wasu dabbobin da aka yi watsi da su babu mai kiwonsu, to babu shakka wannan yana yin karan-tsaye ne ga mulkin Allah da hikimarsa, kuma bai girmama shi yadda ya kamata ba.

2. Alƙur'ani littafi ne mai tarin albarka; cike yake da albishir ga muminai da gidan Aljanna da gafara daga Allah da karantar da kyakkyawar aƙida da kyawawan ayyuka da halaye nagari da gargaɗi a kan munanan aƙidu da ayyukan ɓata da miyagun halaye da kuma bayanin halal da haram. Alƙur'ani dukkansa albarka ne da haske.

3. Duk wanda ya yi imani na gaskiya da ranar lahira, to alaƙarsa da Alƙur'ani za ta yi ƙarfi, ya zama yana tare da shi da koyarwarsa a ko da yaushe.

Suratul An'am (91-92)

وَمَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ قَدۡرِهِۦٓ إِذۡ قَالُواْ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَىٰ بَشَرٖ مِّن شَيۡءٖۗ قُلۡ مَنۡ أَنزَلَ ٱلۡكِتَٰبَ ٱلَّذِي جَآءَ بِهِۦ مُوسَىٰ نُورٗا وَهُدٗى لِّلنَّاسِ تَجۡعَلُونَهُۥ قَرَاطِيسَ تُبۡدُونَهَا وَتُخۡفُونَ كَثِيرٗاۖ وَعُلِّمۡتُم مَّا لَمۡ تَعۡلَمُوٓاْ أَنتُمۡ وَلَآ ءَابَآؤُكُمۡۖ قُلِ ٱللَّهُۖ ثُمَّ ذَرۡهُمۡ فِي خَوۡضِهِمۡ يَلۡعَبُونَ ٩١ وَهَٰذَا كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ مُبَارَكٞ مُّصَدِّقُ ٱلَّذِي بَيۡنَ يَدَيۡهِ وَلِتُنذِرَ أُمَّ ٱلۡقُرَىٰ وَمَنۡ حَوۡلَهَاۚ وَٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦ وَهُمۡ عَلَىٰ صَلَاتِهِمۡ يُحَافِظُونَ ٩٢

91. Kuma ba su girmama Allah haƙiƙanin girman da ya kamace shi ba, yayin da suka ce: "Allah bai saukar wa wani mutum da komai ba." Ka ce: "Wane ne ya saukar da littafin da Musa ya zo da shi, mai haske, kuma mai shiryar da mutane; kuka riƙa mayar da takardunsa falle-falle, kuna bayyana (waɗanda kuke so), kuma kuna ɓoye wani kaso mai yawa; kuma aka sanar da ku abin da ba ku sani ba, ku da ma iyayenku?" Ka ce: "Allah ne (Ya saukar da shi)" Sannan sai ka ƙyale su su yi ta kutsawa cikin ɓarnarsu, suna wasa.

92. Kuma wannan (Alƙur'ani) littafi ne mai albarka, wanda Muka saukar da shi mai gaskata abin da ya gabace shi (na littattafai), kuma don ka gargaɗi uwar alƙaryu (mutanen Makka) da waɗanda suke kewaye da ita. Waɗanda kuwa suke yin imani da ranar lahira, suna yin imani da shi ne (Alƙur'ani), kuma su suna kiyaye sallolinsu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana magana ne da masu musun annabcin Annabi (ﷺ) da ƙaryata wahayin da aka yi masa, inda ya ce, waɗannan kangararru ba su girmama Allah yadda ya

kamata a girmama shi ba, da har suke cewa, wai babu wani ɗan’adam da Allah ya saukar masa da wani littafi ko ya yi masa wahayi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tambaye su, wane ne ya saukar da littafin Attaura wanda Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo wa mutanensa da shi a matsayin haske da shiriya gare su amma suka mayar da shi takardu falle-falle suna bayyana wa mutane abin da suke son su sani, amma suna ɓoye wani sashe mai yawa daga cikinsa wanda ba sa so mutane su gani saboda ya ƙunshi siffofin Manzon Allah (ﷺ) da wasu hukunce-hukunce da ya zo da su, waɗanda suka saɓa wa son ransu? Bugu da ƙari kuma Allah ya sanar da su abin da su da iyayensu a da ba su sani ba. Sai Allah ya umarci Annabi ya ba su amsar waccan tambaya cewa, Allah ne ya yi duk waɗannan abubuwan da aka ambata. Sannan ya umarce shi da ya ƙyale su su yi ta shisshigin su da kutsawa cikin ƙarya da kafirci da izgili, Allah yana ganin su, kuma ba da jimawa ba zai damƙe su da azabarsa.
Sai kuma Allah ya tabbatar da cewa, wannan Alƙur’anin da ya saukar wa Annabi (ﷺ) littafi ne mai albarka, yana kuma gaskata littattafan da suka gabace shi. Kuma ya saukar masa shi ne don ya gargaɗi mutanen Makka da maƙotansu da sauran garuruwa da shi. Sannan ya bayyana cewa, mutanen da suka yarda akwai ranar lahira, sun yarda da wannan Alƙur’anin, kuma suna kula da tsayar da sallolinsu kamar yadda aka umarce su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɓacin aƙidar masu cewa suna karɓar umarni ne a zuciyarsu daga Allah kai-tsaye. Wato suna karɓowa daga inda Mala’ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake karɓowa. Wannan ba shakka kafirci ne.

2. Duk wanda ya ce ana yi masa wahayi bayan Manzon Allah (ﷺ), ko ya yarda da mai faɗar hakan, to ya zama babban azzalumin da babu irinsa, kuma wannan aƙida kafirci ne.

3. Hakanan kafirci ne mutum ya yi da’awar an saukar masa wani abu wanda ya fi Alƙur’ani daraja ko falala.

4. Hakanan duk wanda ya yi da’awar zai kawo wa mutane tsarin rayuwa da ya fi na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ma ya shiga cikin wannan ayar.

5. Bayani a kan wahalhalun mutuwa da azzalumai za su ɗandana a ƙarshen rayuwarsu.6. Tabbatar da azabar ƙabari.

7. Gargaɗi ga masu fifita tara abin duniya su manta da lahirarsu.8. Duk waɗanda suka saki Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) suka riƙe wasu a matsayin masu cetonsu ranar alƙiyama, to sun yi aikin banza domin ba za su tsinana musu komai ba a wannan ranar.

Suratul An’am (93-94)

وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ قَالَ أُوحِيَ إِلَيَّ وَلَمْ يُوحَ إِلَيْهِ شَيْءٌ وَمَن قَالَ سَأُنزِلُ مِثْلَ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ ۗ وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِي غَمَرَٰتِ ٱلْمَوْتِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ بَاسِطُوٓا۟ أَيْدِيهِمْ أَخْرِجُوٓا۟ أَنفُسَكُمُ ۖ ٱلْيَوْمَ تُجْزَوْنَ عَذَابَ ٱلْهُونِ بِمَا كُنتُمْ تَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ غَيْرَ ٱلْحَقِّ وَكُنتُمْ عَنْ ءَايَٰتِهِۦ تَسْتَكْبِرُونَ ﴿٩٣﴾ وَلَقَدْ جِئْتُمُونَا فُرَٰدَىٰ كَمَا خَلَقْنَٰكُمْ أَوَّلَ مَرَّةٍ وَتَرَكْتُم مَّا خَوَّلْنَٰكُمْ وَرَآءَ ظُهُورِكُمْ ۖ وَمَا نَرَىٰ مَعَكُمْ شُفَعَآءَكُمُ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُمْ أَنَّهُمْ فِيكُمْ شُرَكَٰٓؤُا۟ ۚ لَقَد تَّقَطَّعَ بَيْنَكُمْ وَضَلَّ عَنكُم مَّا كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿٩٤﴾

93. Kuma wane ne ya fi zalunci kamar wanda ya ƙagi ƙarya ya jingina wa Allah, ko kuma ya ce: “An yiwo mini wahayi,” alhalin kuma ba a yi masa wahayin komai ba, da kuma wanda ya ce: “Zan saukar da irin abin da Allah Ya saukar?” Kuma da za ka ga lokacin da kafirai suke cikin magagin mutuwa, mala’iku kuma suna miƙa hannayensu suna cewa: “Ku fito da rayukanku (da kanku), a yau ne za a saka muku da azabar wulaƙanci, saboda irin abin da kuke faɗa game da Allah wanda ba gaskiya ba, kuma kun kasance kuna girman kai game da ayoyinsa.”

94. Kuma lalle haƙiƙa kun zo Mana ɗaiɗai kamar yadda Muka halicce ku a karon fari, kuma kun baro abin da Muka ba ku a bayanku (a duniya), kuma har yanzu ba Ma ganin masu ceton ku waɗanda kuka riya cewa su ne abokanan tarayyarku. Lalle haƙiƙa dangantakar da take tsakaninku ta yanke, kuma abin da kuke riyawa ya ɓace muku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, babu babban azzalumi kamar wanda ya ƙagi ƙarya ya jingina wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ko kuma ya bushi iska ya ce Allah ya yi masa wahayi, alhalin ƙarya yake ba wani wahayi da ya yi masa ko kuma ya riƙa cika baki yana cewa, shi ma zai iya saukar da irin abin da Allah ya saukar. Sai kuma Allah ya nusantar da Annabi (ﷺ) cewa, da ya ga azzalumai lokacin da suke cikin magagin mutuwa, da bala’in raɗaɗin fitar rai da baƙin ciki sun taru sun lulluɓe su, da ba shakka ya ga abin mamaki da mawuyacin halin da suke ciki. A lokacin mala’iku ne suke ta jibgar su suna ce musu: “Ku fito da rayukanku da kanku daga gangar jikinku, a yau ne za ku ɗanɗani azabar wulaƙanci da ƙasƙanci sakamakon ƙaryar da kuke yi wa Allah da girman kan da kuke nunawa wanda ya hana ku ku yi imani da ayoyin Allah.”
Sannan a ranar alƙiyama Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai titse su ya ce da su, a wannan rana ga su nan an baje su da ɗai-ɗai kamar yadda aka halicce su da farko, kuma duk ni’imomi da dukiya da ‘ya’ya da suka mora a duniya sun baro su a baya. Kuma waɗanda suke da’awar cewa su abokan tarayyarsu ne waɗanda suka yarda cewa za su cece su a wannan rana duk sun ɓace musu; alaƙar da take tsakaninsu da su gaba ɗaya ta yanke, kuma abin da suka kasance suna riyawa a wannan rana ya ɓace musu ɓat.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duba ga halittar duniya da yin tunani game da tsarinta da yadda take gudana zai tabbatar mana da samuwar Allah mahaliccin kowa da komai da cancantar a bauta masa shi kaɗai, ba tare da wani abokin tarayya ba.

2. Halittar taurari da tsarin gudanarsu a kan wata ajiyayyar ƙa’ida yana tabbatar da Ɗayantakar Allah da girman ikonsa.

3. Allah ya tsara tafiyar rana da wata a kan wata ƙa’ida guda wadda ba ta saɓawa. Wannan wani ƙaƙƙarfan dalili ne a kan cikakken ilimin Allah da ikonsa.

4. Rana da wata da taurari hanyoyi ne na sanin lissafin watanni da shekaru da ilimin falaki.

*إِنَّ ٱللَّهَ فَالِقُ ٱلۡحَبِّ وَٱلنَّوَىٰۖ يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَمُخۡرِجُ ٱلۡمَيِّتِ مِنَ ٱلۡحَيِّۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٩٥ فَالِقُ ٱلۡإِصۡبَاحِ وَجَعَلَ ٱلَّيۡلَ سَكَنٗا وَٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَ حُسۡبَانٗاۚ ذَٰلِكَ تَقۡدِيرُ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡعَلِيمِ ٩٦ وَهُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلنُّجُومَ لِتَهۡتَدُواْ بِهَا فِي ظُلُمَٰتِ ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِۗ قَدۡ فَصَّلۡنَا ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ٩٧ وَهُوَ ٱلَّذِيٓ أَنشَأَكُم مِّن نَّفۡسٖ وَٰحِدَةٖ فَمُسۡتَقَرّٞ وَمُسۡتَوۡدَعٞۗ قَدۡ فَصَّلۡنَا ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَفۡقَهُونَ ٩٨ وَهُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجۡنَا بِهِۦ نَبَاتَ كُلِّ شَيۡءٖ فَأَخۡرَجۡنَا مِنۡهُ خَضِرٗا نُّخۡرِجُ مِنۡهُ حَبّٗا مُّتَرَاكِبٗا وَمِنَ ٱلنَّخۡلِ مِن طَلۡعِهَا قِنۡوَانٞ دَانِيَةٞ وَجَنَّٰتٖ مِّنۡ أَعۡنَابٖ وَٱلزَّيۡتُونَ وَٱلرُّمَّانَ مُشۡتَبِهٗا وَغَيۡرَ مُتَشَٰبِهٍۗ ٱنظُرُوٓاْ إِلَىٰ ثَمَرِهِۦٓ إِذَآ أَثۡمَرَ وَيَنۡعِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكُمۡ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٩٩

95. Lalle Allah ne Yake tsaga ƙwaya da ƙwallon dabino (lokacin tsirowarsa) shi Yake fitar da rayayye daga matacce, kuma Mai fitar da matacce daga rayayye. Mai yin wannan aiki Shi ne Allah; to ta yaya ake kautar da ku?

96. (Shi ne) Mai keto da hasken safiya, kuma Ya sanya dare don nutsuwa; rana da wata kuma don ƙidayar lokatai. Wannan shiri ne na (Allah) Mabuwayi, Mai yawan sani.

97. Kuma Shi ne Wanda Ya sanya muku taurari domin ku gane hanya da su a cikin duffan tudu da na ruwa. Haƙiƙa Mun bayyana ayoyi ga mutanen da suke da sani.

98. Kuma Shi ne Wanda Ya halicce ku daga rai ɗaya, sannan Ya ajiye ku a wani wurin zama (tsatson namiji) da kuma wani wurin ajiya, (mahaifiyar mace). Haƙiƙa Mun bayyana ayoyi ga mutanen da suke fahimta.

99. Kuma Shi ne Wanda Ya saukar da ruwa daga sama, sai Muka fitar da kowane irin dangin tsiro da shi, sannan Muka fitar da shi (tsiron) (wasu) koraye, daga gare shi kuma Muke fitar da ƙwayoyi a cunkushe daga gare shi. Kuma daga hudar dabino (ake samun) nonuna waɗanda suke dab da ƙasa; da kuma waɗansu lambuna na inabi da zaitun da ruman, masu kama da juna da kuma mabambanta. Ku kalli ‘ya’yansu idan suka yi ‘ya’ya da kuma lokacin da suka nuna. Lalle game da wannan akwai ayoyi ga mutanen da suka yi imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cikar ikonsa da hikimarsa da cewa, shi ne yake tsaga ƙwaya ya fitar da shuka daga cikinta, ya kuma tsaga ƙwallon dabino ya fitar da itaciya daga cikinsa. Yana kuma fitar da mai rai daga matacce, ya fitar da matacce daga mai rai, kamar yadda yake fitar da mutum daga ɗigon maniyyi kuma ya fitar da maniyyi daga mutum, ko kaza daga ƙwai ko ƙwai daga kaza. Hakanan kuma shi yake fitar da mumini daga tsatson kafiri, ko ya fitar da kafiri daga tsatson mumini. To wanda yake yin haka fa shi ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to ta yaya ake kautar da kafirai daga gaskiya bayan bayyanar waɗannan hujjoji masu ƙarfi, har su riƙa bautar wasu ba Allah ba?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma shi ne mai keto da hasken safiya daga duhun dare, kuma ya sanya dare ya zamo lokacin samun nutsuwa da hutu ga duk wani mai kujuba-kujuba da rana; rana da wata kuma ya nufa suna gudana a kan wani ƙididdigaggen lissafi wanda ba ya saɓawa. To wannan ƙaddarawa ce ta Allah Mabuwayi mai cikakken sani. Haka kuma ya sanya taurari a matsayin alamu da matafiya suke amfani da su wajen gane hanyoyi a cikin duffan tudu da teku. Haƙiƙa Allah ya bayyana ayoyi daki-daki ga mutane masu ilimi.

Hakanan kuma ya halicci mutane gaba ɗaya daga tsatson Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), shi kuma ya halicce shi ne da tabo tun farko. Amma su mutane daga ɗigon maniyyi ne da Allah ya sanya a tsatson iyayensu, sannan ya zaunar da ɗigon maniyyin a cikin mahaifun iyayensu mata har zuwa lokacin haihuwarsu. Allah yana bayanin ayoyinsa daki-daki ne don mutane masu tunani su fahimci manufofin Ubangiji.
Wata ƙudurar ta Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ita ce saukar da ruwan sama, wanda da shi ne yake fitar da kowanne irin tsiro; daga kowane tsiro ne kuma Allah ya fitar da shukoki da itatuwa koraye, sannan ya halicci ƙwaya da 'ya'yan itatuwa daga waɗannan tsirrai wasu kan wasu, kamar zangarniya da kuma hantsa-hantsa ta dabino daga hudarsa dab da ƙasa mai sauƙin tsinka. Kuma ya fitar da gonaki na inabi da bishiyoyin zaitun da rumman waɗanda ganyayensu suke kama da juna amma 'ya'yansu da ɗanɗanonsu suka sha bamban. Ya kuma umarci bayinsa da su kalli 'ya'yan itatuwan lokacin da suka fito da lokacin girmansu da nunarsu, kallo na tuntuntuni da ɗaukar darasi, domin a cikin waɗannan abubuwa akwai ayoyi ga mutane masu yin imani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Masu ta'ammali da aljannu ta hanyar saba wa Allah sun mayar da su abubuwan tarayya ga Allah, suna bauta musu ba Allah ba.

2. Allah ne mahaliccin kowa da komai, don haka ba zai yiwu a jingina masa ɗa ko mata ba, domin dukansu bayinsa ne; ɗa kuwa ba ya zama bawa na mahaifinsa.

3. Duk wanda ya yarda da *Rububiyyar* Allah, to lalle ne ya amince da Uluhiyyarsa, wato ya bauta masa shi kaɗai, ba tare da ya haɗa shi da abokin tarayya ba.

4. Muminai tabbas za su ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a lahira, kamar yadda dalilai da yawa suka nuna, amma idanu ba za su iya riskar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da kallo ba, kamar yadda wannan ayar ta 103 ta nuna.

Suratul An'am (100-103)

وَجَعَلُواْ لِلَّهِ شُرَكَآءَ ٱلۡجِنَّ وَخَلَقَهُمۡۖ وَخَرَقُواْ لَهُۥ بَنِينَ وَبَنَٰتُۢ بِغَيۡرِ عِلۡمٖۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يَصِفُونَ ١٠٠ بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ أَنَّىٰ
يَكُونُ لَهُۥ وَلَدٞ وَلَمۡ تَكُن لَّهُۥ صَٰحِبَةٞۖ وَخَلَقَ كُلَّ شَيۡءٖۖ وَهُوَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١٠١ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖ
فَٱعۡبُدُوهُۚ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٞ ١٠٢ لَّا تُدۡرِكُهُ ٱلۡأَبۡصَٰرُ وَهُوَ يُدۡرِكُ ٱلۡأَبۡصَٰرَۖ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلۡخَبِيرُ ١٠٣ وَجَعَلُواْ لِلَّهِ شُرَكَآءَ ٱلۡجِنَّ وَخَلَقَهُمۡۖ
وَخَرَقُواْ لَهُۥ بَنِينَ وَبَنَٰتُۢ بِغَيۡرِ عِلۡمٖۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يَصِفُونَ ١٠٠ بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ أَنَّىٰ يَكُونُ لَهُۥ وَلَدٞ وَلَمۡ تَكُن لَّهُۥ صَٰحِبَةٞۖ
وَخَلَقَ كُلَّ شَيۡءٖۖ وَهُوَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١٠١ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖ فَٱعۡبُدُوهُۚ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٞ ١٠٢ لَّا
تُدۡرِكُهُ ٱلۡأَبۡصَٰرُ وَهُوَ يُدۡرِكُ ٱلۡأَبۡصَٰرَۖ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلۡخَبِيرُ ١٠٣

100. Kuma sun sanya wa Allah aljannu a matsayin abokanan tarayya, alhali kuwa Shi ya halicce su; kuma suka ƙago masa 'ya'ya maza da mata, ba tare da wani ilimi ba. Tsarki ya tabbata a gare Shi, kuma Ya ɗaukaka daga irin abin da suke siffanta (Shi da shi).

101. (Shi ne) Maƙagin sammai da ƙasa; ta yaya zai zama Yana da ɗa, ga Shi kuma ba Shi da mata? Kuma Shi ne Ya halicci komai, kuma Shi Masanin komai ne.

102. Wannan Shi ne Allah Ubangijinku; ba wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; Mahaliccin komai, don haka ku bauta masa. Kuma Shi Mai kiyayewa ne da komai.

103. Gannai ba sa riskar Sa, Shi ne Yake riskar gannai, kuma Shi Mai tausasawa ne, Mai cikakken sani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa, mushirikai sun mayar da aljannu ababen bauta tare da Allah, alhalin shi ya halicce su, maimakon su bauta wa Allah mahaliccin kowa da komai. Sun kuma ƙira wa Allah ƙaryar cewa yana da 'ya'ya maza da mata, ba tare da suna da wata hujja a kan haka ba, don kawai jahilci da rashin sanin girman Allah. Allah ya tsarkaka, kuma ya ɗaukaka daga duk abin da waɗannan mushirikai suke siffanta shi da shi.
Shi ne kuma wanda ya ƙagi halittar sammai da ƙasa ba tare da ya kwaikwaya a wurin wani ba; ta yaya kuma za a ce yana da ɗa ko mata, alhali shi ne ya halicci komai? Don haka shi cikakken mawadaci ne, ba shi da buƙatar komai a wurin wani mahaluƙi, shi ne wanda ake da buƙata a wurinsa, kuma shi ne masanin komai, babu abin da yake ɓoye masa.
To wannan fa shi ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda shi kaɗai ya cancanta a bauta wa, shi ne Ubangijin talikai, babu wani abin bauta da gaskiya sai shi, mahaliccin komai. Don haka sai kowa ya bauta masa, ya amince da Kaɗaitakarsa, kuma shi wakili ne a kan komai; idanu kuma ba za su iya riskar sa da kallo ba, shi ne wanda iliminsa da jinsa da ganinsa suka kewaye komai, kuma shi ne mai tausasawa, mai cikakken sani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kauce wa ra'ayin riƙau da tashi a yi bincike a kan dalili na ilimi don tabbatar da gaskiya da gane ƙarya da kauce mata.

2. Mai kira zuwa ga Allah yana da kyau ya riƙa bin salo iri-iri don bayanin gaskiyar da yake ɗauke da ita, tare da la'akari da bambance-bambancen hankulan mutane da yi musu bayani gwargwadon hankalin kowa.

3. Mai kira zuwa ga Allah kada ya ƙwallafa ransa a kan sai ya shiryar da wasu mutane da suka riga suka bijire, suka kulle duk wata ƙofa ta fahimta tsakaninsa da su. Ya mai da hankalinsa ga kiran waɗanda suke sauraron sa, suke kuma shirye da su karɓi gaskiya idan sun fahimce ta.

4. Kasancewar Allah shi kaɗai ya cancanci a bauta masa, to ya zama wajibi a yi masa biyayya, kada a kauce wa umarninsa saboda jahilcin jahilai ko wautar wawaye.

Suratul An'am (104-107)

قَدْ جَآءَكُم بَصَآئِرُ مِن رَّبِّكُمْۖ فَمَنْ أَبْصَرَ فَلِنَفْسِهِۦۖ وَمَنْ عَمِىَ فَعَلَيْهَاۚ وَمَآ أَنَا۠ عَلَيْكُم بِحَفِيظٍ ﴿١٠٤﴾ وَكَذَٰلِكَ نُصَرِّفُ ٱلْـَٔايَٰتِ وَلِيَقُولُوا۟ دَرَسْتَ وَلِنُبَيِّنَهُۥ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿١٠٥﴾ ٱتَّبِعْ مَآ أُوحِىَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ وَأَعْرِضْ عَنِ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٠٦﴾ وَلَوْ شَآءَ ٱللَّهُ مَآ أَشْرَكُوا۟ۖ وَمَا جَعَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ حَفِيظًاۖ وَمَآ أَنتَ عَلَيْهِم بِوَكِيلٍ ﴿١٠٧﴾

104. Haƙiƙa hujjoji sun zo muku daga Ubangijinku; don haka duk wanda ya gan su (ya bi su), to ya yi don amfanin kansa ne; duk kuwa wanda ya makance, to kansa ya cuta. Kuma ni ba mai tsaron ku ba ne.

105. Kuma kamar haka ne Muke bayyana ayoyi, don (kafirai) su ce: “Ka koya ne (daga wasu littattafai)”, kuma don Mu bayyana shi (Alƙur’ani) ga mutanen da suke ganewa.

106. Ka bi abin da aka yi maka wahayi daga Ubangijinka; ba abin bautawa da gaskiya sai Shi; kuma ka kawar da kai daga mushrikai.

107. Kuma da Allah Ya ga dama, da ba su yi shirka ba. Ba Mu kuma sanya ka mai tsaro a kansu ba; kuma kai ba wakili ne a gare su ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tabbatar wa mutane cewa, bayyanannun dalilai da ƙarfafan hujjoji a kan gaskiyar Alƙur’ani sun zo musu; a cikinsu Allah ya bayyana ƙudurarsa da cikakken ikonsa. Duk wanda ya fahimci waɗannan hujjoji, ya yi imani da su, to kansa ne zai amfana, duk wanda kuma ya ƙi imani da su, ya yi watsi da abin da suke tabbatarwa, to kansa kaɗai zai cutar, Manzon Allah (ﷺ) ba shi ne mai tsaron su ko wanda yake lissafa ayyukansu ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma yana bayyana hujjoji da dalilai ta hanyoyi daban-daban a wannan Surar, domin tabbatar da Tauhidin Ubangiji. Da ma kuma Allah ya saba yin bayanin ayoyinsa ga mutane ta hanyoyi daban-daban a cikin wannan Alƙur’ani, domin kawar da zargin duk wani wanda zuciyarsa ta makance mai cewa, wai Annabi (ﷺ) ya koyo wannan Alƙur’ani ne daga malaman Yahudawa ko Nasara. Kuma Allah Ta’ala yana yin waɗannan bayanai ne domin mutane masu ilimi su fahimta, kuma su karɓa su yi aiki da su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) cewa, ya bi tafarkin Alƙur’ani wanda ya yi masa wahayinsa, tafarkin da yake tabbatar da Allah shi kaɗai ne abin bauta, babu wani abin bautawa ba shi ba, ya kuma umarce shi da ya yi watsi da tafarkin mushirikai masu haɗa Allah da wani cikin bauta.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, da ya ga dama da sai ya ɗora mushirikai a kan hanyar shiriya, sai dai kuma Allah bai nufe su da shiriya ba, sai suka taɓe. Kuma ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, bai saka shi mai tsaron kafirai, ya sa ido a kan ayyukansu ko rayuwarsu ba; wannan aikin Allah ne. Kuma bai wakilta shi a kan yi musu hisabi na ayyukan da suke yi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan wani aikin zai jawo saɓon Allah, to wajibi ne a ƙyale shi.

2. Idan abokin husuma ya yi maka wauta da rashin hankali, to kai bai dace ka yi irin yadda ya yi ba, sai ku zama ɗaya.

3. Koyarwa ga mai da’awa zuwa ga Allah da cewa, kada ya ɓata lokacinsa a kan abubuwan da ba su da wani amfani gare shi ko ga da’awarsa.4. Wanda ya ƙi gaskiya, ya bijire mata, ya bi son zuciyarsa, wannan zai gadar masa da makantar zuciya, ya kasa tantance ƙarya da gaskiya sakamakon taurin kansa na fari.

5. Kamar yadda aikin alheri yake haifar da wani aikin alherin, haka aikin laifi yake haifar wa da mai shi wani laifin, har laifukansa su yi ta hauhawa su toshe masa zuciya, ya kasa fahimtar gaskiya komai bayyanarta.

وَلَا تَسُبُّواْ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ فَيَسُبُّواْ ٱللَّهَ عَدۡوَۢا بِغَيۡرِ عِلۡمٖۗ كَذَٰلِكَ زَيَّنَّا لِكُلِّ أُمَّةٍ عَمَلَهُمۡ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّهِم مَّرۡجِعُهُمۡ فَيُنَبِّئُهُم بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٠٨ وَأَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ لَئِن جَآءَتۡهُمۡ ءَايَةٞ لَّيُؤۡمِنُنَّ بِهَاۚ قُلۡ إِنَّمَا ٱلۡأٓيَٰتُ عِندَ ٱللَّهِ وَمَا يُشۡعِرُكُمۡ أَنَّهَآ إِذَا جَآءَتۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ١٠٩ وَنُقَلِّبُ أَفۡـِٔدَتَهُمۡ وَأَبۡصَٰرَهُمۡ كَمَا لَمۡ يُؤۡمِنُواْ بِهِۦٓ أَوَّلَ مَرَّةٖ وَنَذَرُهُمۡ فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ١١٠

108. Kuma kada ku zagi waɗanda suke bauta wa ba Allah ba, sai su zagi Allah saboda zalunci, ba tare da sanin (girmansa) ba. Kamar haka ne Muka ƙawata wa kowace al’umma ayyukansu (nagari da munana), sannan zuwa ga Ubangijinsu ne makomarsu take, sai Ya ba su labarin abin da suka kasance suna aikatawa.

109. Kuma sun rantse da Allah iyakar gaskiyarsu cewa, lalle idan har aya ta zo musu, tabbas za su yi imani da ita. Ka ce: “Ai ayoyi daga wajen Allah suke.” Kuma wa ya sanar da ku cewa, idan (ayoyin) sun zo ba za su yi imani ba?

110. Kuma za Mu riƙa jujjuya zukatansu da gannansu, (daga fahimta da ganin gaskiya) kamar yadda ba su yi imani da shi ba da farko, Mu kuma bar su cikin shisshiginsu suna ɗimuwa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana muminai su zagi abin bautar wasu don kada su ma su rama su zagi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) saboda rashin sanin girmansa. Kamar yadda Allah ya ƙawata wa waɗannan mushirikan ayyukan da suke yi na shirka, hakanan ya ƙawata wa kowace al’umma ayyukanta. Sannan makomarsu gaba ɗaya zuwa ga Allah ne, zai kuma labarta musu duk abin da suka aikata kuma ya yi musu sakayya a kai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, mushirkai sun rantse iya rantsuwarsu cewa, idan wata mu’ujiza da suka nema ta zo musu, to lalle za su yi imani da ita cewa daga Allah take. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, mu’ujizoji duka suna hannun Allah, shi ne idan ya ga dama zai nuna musu ita, idan kuma ya ga dama ya ƙi amsa buƙatarsu. Sai kuma Allah ya ankarar da muminai cewa, wa ya sanar da su cewa idan mu’ujizar ta zo za su ba da gaskiya su yi imani da ita?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, shi ne mai jujjuya zukatansu da gannansu su kasa fahimtar gaskiya, su kuma kasa ganin ta, saboda sun ƙi yin imani da Alƙur’ani tun lokacin da Annabi (ﷺ) ya zo musu da shi, kuma Allah zai ƙyale su cikin shisshiginsu da taurin kansu suna ta ɗimuwa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Zukatan ‘yan’adam gaba ɗaya suna tsakanin ‘yan yatsu biyu na Allah mai rahama ne, kamar zuciya ɗaya, yana jujjuya ta yadda ya ga dama.” Sai kuma Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ya Allah mai jujjuya zukata, ka juya zukatanmu a kan ɗa’arka.” [Muslim #2654].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani mai taurin kan karɓar gaskiya, yana faɗa da masu kira zuwa gaskiya, to wannan maƙiyinsu ne.

2. Mumini ya yi imanin cewa, duk yadda maƙiyin Allah ya kai ga ƙarfi ko isa, to Allah ya fi ƙarfinsa, kuma shi ne zai ba wa mai gaskiya kariya daga sharrinsa.

3. A yi hattara da Shaiɗan, domin yakan yi amfani da wasu kalmomi masu daɗin ji ya jefa su a kunnuwan mumini don ya cutar da shi ya yi ƙoƙarin lullube ƙarya da ɓarna da su. Idan mumini bai yi hattara ba sai nan da nan ya ruɗu da su, ya auka cikin ɓarna bai ankara ba.

4. Maƙiya gaskiya sukan haɗa kansu wajen yaƙar ta da ƙoƙarin kawar da ita.

5. Rashin imani da ranar lahira da saɓa wa annabawan Allah wasu abubuwa ne biyu da suke haɗe da juna, watau duk wanda bai yi imani da ranar lahira ba, to ba zai amsa kiran annabawa ba.

Suratul An'am (111-113)

*وَلَوۡ أَنَّنَا نَزَّلۡنَآ إِلَيۡهِمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ وَكَلَّمَهُمُ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَحَشَرۡنَا عَلَيۡهِمۡ كُلَّ شَيۡءٖ قُبُلٗا مَّا كَانُواْ لِيُؤۡمِنُوٓاْ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ يَجۡهَلُونَ١١١ وَكَذَٰلِكَ جَعَلۡنَا لِكُلِّ نَبِيّٖ عَدُوّٗا شَيَٰطِينَ ٱلۡإِنسِ وَٱلۡجِنِّ يُوحِي بَعۡضُهُمۡ إِلَىٰ بَعۡضٖ زُخۡرُفَ ٱلۡقَوۡلِ غُرُورٗاۚ وَلَوۡ شَآءَ رَبُّكَ مَا فَعَلُوهُۖ فَذَرۡهُمۡ وَمَا يَفۡتَرُونَ١١٢ وَلِتَصۡغَىٰٓ إِلَيۡهِ أَفۡـِٔدَةُ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ وَلِيَرۡضَوۡهُ وَلِيَقۡتَرِفُواْ مَا هُم مُّقۡتَرِفُونَ١١٣

111. Kuma Mu ɗin nan da a ce lalle za Mu saukar musu da mala'iku, kuma matattu su yi musu magana, kuma Mu tattaro musu komai a gabansu, to da ba za su taɓa yin imani ba, sai dai idan Allah Ya ga dama, amma yawancinsu suna jahilta ne.

112. Kuma kamar haka ne Muka sanya wa kowane annabi maƙiya daga shaiɗanun mutane da aljannu, sashinsu yana kimsa wa wani sashi ƙayataccen zance, don ruɗi. Kuma da Ubangijinka Ya ga dama da ba su aikata haka ba; don haka ka ƙyale su da irin abin da suke ƙagowa.

113. Don kuma zukatan waɗanda ba su yi imani da lahira ba su karkata zuwa gare shi, kuma su yarda da shi (ruɗin) kuma su ci gaba da ƙago abin da suke ƙagowa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, da ya amsa buƙatar masu neman a nuna musu wata mu'ujiza mai tabbatar da gaskiyar Manzon Allah (ﷺ), da Allah ya amsa musu ya saukar musu da mala'iku su gan su ƙuru-ƙuru, ko ya tayar musu da matattu su sanar da su cewa, Annabi Manzon Allah ne da gaske, ko kuma ya tattara musu duk wata halitta dodo dodo a gabansu su gaya musu gaskiyar annabtar Annabi (ﷺ), to da ba za su ba da gaskiya ba sai Allah ya ga dama, sai dai kuma yawancinsu suna jahiltar hakan.
Sai kuma Allah ya bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, kamar yadda ya jarrabe shi da maƙiya cikin mutane da aljannu waɗanda suke faɗa da shi da da'awarsa, to hakanan ya jarrabi sauran annabawa da maƙiya irin waɗannan.
Ya zo cikin hadisin A'isha (Allah ya kara mata yarda) cewa, Waraƙatu ɗan Naufalu ya faɗa wa Annabi (ﷺ) lokacin da Nana Khadija (Allah ya kara mata yarda) ta je da shi wajensa cewa: "Babu wani mutum da ya zo da irin abin da ka zo da shi, face sai an yi gaba da shi." [Bukhari #3, da Muslim #160].
Shaiɗanun aljannu a cikinsu suna kimsa wa shaiɗanun mutane maganganu na ƙarya waɗanda suke ƙawata kalmominsu don ruɗar mutane da su. Da Allah ya ga dama da ba za su yi hakan ba, sai dai ya riga ya ƙaddara komai yadda hikimarsa ta gudana. Sai kuma ya umarci Annabinsa (ﷺ) cewa, ya ƙyale su, ya kuma yi watsi da ƙarairayinsu da suke ƙagawa.

Hakanan shaiɗanun aljannu suna saƙa wa shaiɗanun mutane wasu ƙawatattun maganganu na ƙarya domin zukatan waɗanda ba su yi imani da lahira ba su karkata gare su, kuma su yarda da su, kuma su aikata abin da za su aikata na kafirci da saɓon Allah a sanadiyarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai ne mai yanke hukunci a kan abin da mutane suke rigima a kansa na sha'anin aƙidu ko shari'a.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin komai na shari'a a cikin littafinsa Alƙur'ani filla-filla ta yadda kowa zai fahimta ya yi aiki da su.

3. Duk labarin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa a littafinsa gaskiya ne, hakanan duk wani hukunci da ya zo da shi cikakken adalci ne a kowane zamani, kuma a kowace al'umma.

4. Yawan mabiya wata aƙida ko wani addini ko wani ra'ayi ba shi ne dalilin da yake nuna wannan gaskiya ne ba; ana sanin gaskiya ne da ƙarfin hujja ba da yawan mabiya ba.

5. Yawancin mutane a duniya ba sa a kan tafarkin gaskiya. Mabiya gaskiya a koyaushe 'yan kaɗan ne.

Suratul An'am (114-117)

أَفَغَيۡرَ ٱللَّهِ أَبۡتَغِي حَكَمٗا وَهُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ إِلَيۡكُمُ ٱلۡكِتَٰبَ مُفَصَّلٗاۚ وَٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَعۡلَمُونَ أَنَّهُۥ مُنَزَّلٞ مِّن رَّبِّكَ بِٱلۡحَقِّۖ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡمُمۡتَرِينَ ١١٤ وَتَمَّتۡ كَلِمَتُ رَبِّكَ صِدۡقٗا وَعَدۡلٗاۚ لَّا مُبَدِّلَ لِكَلِمَٰتِهِۦۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ١١٥ وَإِن تُطِعۡ أَكۡثَرَ مَن فِي ٱلۡأَرۡضِ يُضِلُّوكَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَإِنۡ هُمۡ إِلَّا يَخۡرُصُونَ ١١٦ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعۡلَمُ مَن يَضِلُّ عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِٱلۡمُهۡتَدِينَ ١١٧

114. (Ka ce) "Shin wanin Allah zan nema a matsayin mai yi mana hukunci, alhalin Shi ne wanda Ya saukar muku da littafi mai bayani dalla-dalla?" Waɗanda Muka ba su littafi kuwa suna sane da cewa, lalle shi saukakke ne daga Ubangijinka da gaskiya; don haka lalle kada ka kasance daga cikin masu kokwanto.

115. Kuma kalmomin Ubangijinka cike suke da gaskiya da adalci. Babu kuma mai canza kalmominsa; kuma Shi ne Mai ji, Masani.
116. Kuma in da za ka yi biyayya ga mafiya yawan waɗanda suke a bayan ƙasa to za su ɓatar da kai daga tafarkin Allah. Babu abin da suke bi face zato, kuma ba abin da suke yi face ƙarya.

117. Lalle Ubangijinka Shi ne Mafi sanin waɗanda suke ɓace wa tafarkinsa, kuma Shi ne Mafi sanin shiryayyu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabinsa (ﷺ) ya tambayi mushirikai cewa, wanin Allah suke so ya nema a matsayin mai yi masa hukunci, alhalin shi ne ya saukar masa da littafin Alƙur'ani, wanda yake cike da bayanan hukunce-hukunce daki-daki, har da bayanin abin da suke jayayya a kansa na lamarin aƙida da shari'a? Hasali ma Yahudawa da Allah ya ba su ilimin Attaura sun san cewa Alƙur'ani gaskiya ne daga Allah yake. Sai kuma ya hane shi da yin shakkar komai game da

Alƙur’ani. Duk da cewa an yi wannan hani ne ga Annabi (ﷺ), amma ana nufin al’ummarsa, domin shi ba zai taɓa shakka ba game da kasancewar Alƙur’ani wahayi ne daga Allah zuwa gare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, kalmominsa cikakku ne babu tawaya a cikinsu, kuma suna ƙunshe da labaru na gaskiya da kuma hukunce-hukunce na cikakken adalci, don haka babu wata damar canza wani abu daga kalmominsa (Mai tsarki da ɗaukaka); shi kuma mai jin duk maganganun bayinsa ne, kuma masanin ayyukansu, zai kuma saka musu gwargwadon ayyukansu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fuskantar da maganarsa ga Annabi (ﷺ) da cewa, idan da zai yi biyayya ga yawancin mutanen duniya, to ba shakka da za su ɓatar da shi daga kan addinin Allah, domin kuwa ba wani abu suke bi ba sai zace-zacen ƙarya da shaci-faɗi.
Sai kuma ya tabbatar da cewa, ya fi kowa sanin wanda ya kauce wa shiriya, ya kuma fi kowa sanin shiryayyu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ayyukan Musulmi su saɓa da na mutanen jahiliyya.

2. Shari’ar Musulunci ta bambance tsakanin dabbar da aka yanka ta da sunan Allah da wadda ba a yanka ta da sunansa ba. Wannan yana nuna sunayen Allah masu albarka ne.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin abubuwan da ya haramta dalla-dalla; wannan yana nuna abin da ba a haramta shi ba, to halal ne.

4. Abubuwan da aka halatta sun fi abubuwan da aka haramta yawa, shi ya sa ba zai yiwu a ambace su dalla-dalla ba saboda yawansu. Wannan yana nuna sauƙin shari’ar Musulunci.

5. Bayanin sauƙin shari’ar Musulunci, shi ya sa haramun yakan zamo halal yayin da aka shiga halin larura.

6. Gargaɗi game da bin masu bin soye-soyen zukata, domin duk wanda ya bi su, to za su halakar da shi.

7. Alamar ɓatattu ita ce barin hujja da bin son zuciya.

8. Ba ya halatta ga Musulmi ya riƙa aiki da abin da zuciyarsa take saƙa masa, ba tare da ya auna shi da mizanin shari’a ba, domin yin hakan aiki ne da wahayin shaiɗanu.

9. Duk wanda ya halatta wani abu da Allah ya haramta shi ƙarara ko ya haramta abin da Allah ya halatta shi ƙarara, to ya zama mushiriki.

10. Biyayya ga wanin Allah a kan canza shari’ar Allah shirka ce.

Suratul An’am (118-121)

فَكُلُواْ مِمَّا ذُكِرَ ٱسۡمُ ٱللَّهِ عَلَيۡهِ إِن كُنتُم بِـَٔايَٰتِهِۦ مُؤۡمِنِينَ ١١٨ وَمَا لَكُمۡ أَلَّا تَأۡكُلُواْ مِمَّا ذُكِرَ ٱسۡمُ ٱللَّهِ عَلَيۡهِ وَقَدۡ فَصَّلَ لَكُم مَّا حَرَّمَ عَلَيۡكُمۡ إِلَّا مَا ٱضۡطُرِرۡتُمۡ إِلَيۡهِۗ وَإِنَّ كَثِيرٗا لَّيُضِلُّونَ بِأَهۡوَآئِهِم بِغَيۡرِ عِلۡمٍۗ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعۡلَمُ بِٱلۡمُعۡتَدِينَ ١١٩ وَذَرُواْ ظَٰهِرَ ٱلۡإِثۡمِ وَبَاطِنَهُۥٓۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَكۡسِبُونَ ٱلۡإِثۡمَ سَيُجۡزَوۡنَ بِمَا كَانُواْ يَقۡتَرِفُونَ ١٢٠ وَلَا تَأۡكُلُواْ مِمَّا لَمۡ يُذۡكَرِ ٱسۡمُ ٱللَّهِ عَلَيۡهِ وَإِنَّهُۥ لَفِسۡقٞۗ وَإِنَّ ٱلشَّيَٰطِينَ لَيُوحُونَ إِلَىٰٓ أَوۡلِيَآئِهِمۡ لِيُجَٰدِلُوكُمۡۖ وَإِنۡ أَطَعۡتُمُوهُمۡ إِنَّكُمۡ لَمُشۡرِكُونَ ١٢١

118. To ku ci abin da aka ambaci sunan Allah a kansa (lokacin yankansa), in har kun kasance masu imani da ayoyinsa.

119. Kuma me ya sa ba za ku ci abin da aka ambaci sunan Allah a kansa ba, alhali Ya bayyana muku abin da Ya haramta muku, sai fa abin da kuka matsu game da shi? Kuma lalle yawancinsu ba shakka suna ɓatar da waɗansu ne ta hanyar bin son zuciyarsu, ba tare da ilimi ba. Lalle Ubangijinka Shi ne Mafi sanin masu ƙetare iyaka.

120. Kuma ku bar (aikata) laifuka na sarari da na ɓoye. Haƙiƙa waɗanda suke aikata saɓo, za a saka musu da irin abin da suke aikatawa.

121. Kuma kada ku ci daga abin da ba a ambaci sunan Allah a kansa ba, kuma lalle shi tabbas fasiƙanci ne. Haƙiƙa shaiɗanu tabbas suna kimsa wa masoyansu, don su yi jayayya da ku; idan kuwa kuka bi su to lalle tabbas ku mushirikai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin hukuncin yankan dabba ne da kuma mayar da martani ga mushirikan Larabawa masu yanka dabbobinsu da sunan gumakansu a madadin sunan Allah. Ya umarci bayinsa muminai da su ci abin da aka yanka da sunan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) idan har sun yi imani da ayoyinsa da hujjojin da ya saukar musu a Alƙur'ani da kuma bayanan da Manzon Allah (ﷺ) yake yi musu. Ya kuma ƙara da cewa, me zai hana su cin dabbar da aka yanka ta da sunan Allah, alhalin ya riga ya yi musu bayani filla-filla na abubuwan da aka haramta musu cin su in dai ba bisa larura ba? Ya bayyana cewa, da yawan mutane suna ɓacewa kuma suna ɓatar da wasu ba tare da wata hujja ba, kuma Allah ne mafi sanin masu ƙetare iyakokinsa, su haramta abin da bai haramta ba. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa bayinsa kashedi da su guji saɓa masa a fili ko a ɓoye. Ya bayyana cewa, duk wanda ya saɓa wa wannan umarni nasa, ya aikata laifi, to zai ga sakamakon laifinsa. Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana bayinsa cin naman dabbar da ba a yanka ta da sunansa ba, domin cin namanta rashin biyayya ne gare shi. Ya kuma bayyana cewa, shaiɗanu suna jefa wa 'yan'uwansu mushirikai wani nau'i na ruɗani don su riƙa jayayya da muminai da su. Sukan yi wa muminai zolaya da cewa: "Shin yanzu ku kun yarda ku ci dabbar da kuka kashe da hannunku, amma ba ku yarda ku ci wadda Allah ya kashe da kansa ba?" Wato suna nufin mushen dabbobi.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Larabawa mushirikai suna cewa: "Duk abin da aka yanka shi da sunan Allah kada ku ci, amma ku ci wanda ba a ambaci sunan Allah ba lokacin yankansa." Sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Kuma kada ku ci abin da ba a ambaci sunan Allah a kansa ba." [Abu Dawuda #2818, da Ibni Majah #3173].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa wa muminai cewa, idan har suka yarda suka yi biyayya ga mushirikai, suka halatta cin mushe da abin da Allah ya haramta musu, to su ma sun zama mushirikai kamarsu.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wasu mutane sun zo wajen Manzon Allah (ﷺ) suka ce masa: "Ya Manzon Allah, yanzu ma riƙa cin abin da muka kashe, amma kuma ba za mu ci abin da Allah ya kashe ba?" Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyi." [Tirmizi #3069].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani a zuciyar bawa shi ne rayuwarsa, kafiri kuma matacce ne a wurin Allah.

2. Wanda ya karɓi shiriyar da Annabi (ﷺ) ya zo da ita shi ne yake cikin haske, saɓanin wanda ya bijire mata, ya ƙi imani da ita.

3. Amfanin mumini bai taƙaita a kansa shi kaɗai ba; yana amfanar da sauran mutane da yake cikinsu.

4. Manya-manyan masu laifi a cikin wannan al'umma su ne shuwagabanni masu kwaɗayin mulki da tara abin duniya. Sukan ƙulla wa al'ummominsu makirce-makirce iri-iri domin cim ma manufarsu ta siyasa da bautar da jama'arsu.

5. Tarihi ya nuna cewa, shugabanni marasa gaskiya su ne farkon waɗanda suka riƙa faɗa da manzannin da Allah ya aiko musu domin tabbatar da gyara a rayuwar ɗan'adam, su ne kuma masu faɗa da duk wasu masu ƙoƙarin kawo gyara a cikin al'ummominsu.

6. Bai dace masu kira zuwa ga gaskiya su karaya ba don ganin makirce-makircen wasu manyan masu laifi, domin su ne daga ƙarshe za su faɗa cikin duk wani ramin muguntan da suka haƙa wa masu ƙoƙarin kawo gyara.

7. Manzanci falala ce daga Allah, shi yake zaɓar wanda ya ga dama ya aiko, ba neman sa ake yi ba.

8. A hannun Allah shiriyar bayi take, shi ne yake shiryar da wanda ya ga ya dace da wannan shiriyar, ya ɓatar da wanda ya cancanci ɓatarwa.

9. Gidan Aljanna gida ne da babu wani abin kushewa a ciki.

Suratul An'am (122-127)

أَوَ مَن كَانَ مَيْتًا فَأَحْيَيْنَٰهُ وَجَعَلْنَا لَهُۥ نُورًا يَمْشِى بِهِۦ فِى ٱلنَّاسِ كَمَن مَّثَلُهُۥ فِى ٱلظُّلُمَٰتِ لَيْسَ بِخَارِجٍ مِّنْهَا ۚ كَذَٰلِكَ زُيِّنَ لِلْكَٰفِرِينَ مَا
كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٢٢﴾ وَكَذَٰلِكَ جَعَلْنَا فِى كُلِّ قَرْيَةٍ أَكَٰبِرَ مُجْرِمِيهَا لِيَمْكُرُوا۟ فِيهَا ۖ وَمَا يَمْكُرُونَ إِلَّا بِأَنفُسِهِمْ وَمَا يَشْعُرُونَ ﴿١٢٣﴾ وَإِذَا جَآءَتْهُمْ ءَايَةٌ
قَالُوا۟ لَن نُّؤْمِنَ حَتَّىٰ نُؤْتَىٰ مِثْلَ مَآ أُوتِىَ رُسُلُ ٱللَّهِ ۘ ٱللَّهُ أَعْلَمُ حَيْثُ يَجْعَلُ رِسَالَتَهُۥ ۗ سَيُصِيبُ ٱلَّذِينَ أَجْرَمُوا۟ صَغَارٌ عِندَ ٱللَّهِ وَعَذَابٌ شَدِيدٌۢ
بِمَا كَانُوا۟ يَمْكُرُونَ ﴿١٢٤﴾ فَمَن يُرِدِ ٱللَّهُ أَن يَهْدِيَهُۥ يَشْرَحْ صَدْرَهُۥ لِلْإِسْلَٰمِ ۖ وَمَن يُرِدْ أَن يُضِلَّهُۥ يَجْعَلْ صَدْرَهُۥ ضَيِّقًا حَرَجًا كَأَنَّمَا يَصَّعَّدُ فِى
ٱلسَّمَآءِ ۚ كَذَٰلِكَ يَجْعَلُ ٱللَّهُ ٱلرِّجْسَ عَلَى ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٢٥﴾ وَهَٰذَا صِرَٰطُ رَبِّكَ مُسْتَقِيمًا ۗ قَدْ فَصَّلْنَا ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَذَّكَّرُونَ ﴿١٢٦﴾ ۞ لَهُمْ دَارُ
ٱلسَّلَٰمِ عِندَ رَبِّهِمْ ۖ وَهُوَ وَلِيُّهُم بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٢٧﴾

122. Shin yanzu wanda ya kasance matacce (kafiri), sai Muka rayar da shi, kuma Muka sanya masa haske (na shiriya), yana tafiya da shi cikin mutane, (yanzu) zai zama kamar wanda yake cikin duhu (na kafirci), ta yadda ba zai iya fita daga cikinsa ba? Kamar haka ne aka ƙawata wa kafirai abin da suka kasance suna aikatawa.

123. Kuma kamar haka ne a cikin kowace ƙasa Muka sanya manyan masu laifinta, don su yi makirci a cikinta; kuma ba wanda suke ƙulla wa makirci sai kawunansu, amma su ba sa jin (haka).

124. Kuma idan wata aya ta zo musu, sai su ce: “Ba za mu yi imani ba, har sai an ba mu kwatankwacin abin da aka ba wa manzannin Allah.” Ai Allah Shi ne Mafi sanin inda ya dace Ya sanya manzancinsa. Da sannu ƙaskanci daga Allah zai auka wa waɗanda suka aikata manyan laifuka da kuma azaba mai tsanani, saboda abin da suka kasance suna shiryawa na makirci.

125. Sannan duk wanda Allah Ya yi nufin shiryar da shi, sai Ya yalwata ƙirjinsa ga karɓar Musulunci. Duk wanda kuwa Ya yi nufin Ya ɓatar da shi, sai Ya sanya ƙirjinsa a ƙuntace ainun kamar wanda yake yunƙurin hawa sama. Kamar haka ne Allah Yake sanya ɓata a kan waɗanda ba sa yin imani.

126. Kuma wannan shi ne tafarkin Ubangijinka miƙaƙƙe. Haƙiƙa Mun bayyana ayoyi ga mutanen da suke tuntuntuni.

127. Suna da gida na aminci a wurin Ubangijinsu, kuma Shi ne Majiɓincinsu, saboda abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yin gwaji tsakanin mutumin da yake kafiri, yana fagamniya cikin duhun ɓata da jahilci, sai Allah ya shiryar da shi ya musulunta, ya raya masa zuciya da imani, ya sanya masa haske na shiriya, yana tafiya da shi a cikin mutane; wannan ba zai taɓa zama daidai da wanda ya ci gaba da rayuwa cikin duhun kafirci da jahilci, ya kasa fita daga cikinsa ba.
Kamar yadda aka ƙawata wa kafirai masu jayayya a kan cin mushe ayyukansu na jahiliyya, har suke ganin su kyawawa, to hakanan aka ƙawata wa masu kafirce wa Allah da ayoyinsa munanan aƙidunsu da ayyukansu na ɓata.
Haka kuma a cikin kowace al’umma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya manyan masu laifi, waɗanda suke kiran mutanensu zuwa ɓata da kafirci, suke hana su bin addinin Allah da karɓar gaskiya. To duk wani makirci da suke ƙullawa kansu zai dawo, su ne ba su fahimci haka ba. Kuma idan wata hujja mai ƙarfi ta zo wa waɗannan manyan masu laifin, tana tabbatar da gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ), sai su sa ƙafa su shure ta, su ce su ba za su taɓa yarda ba har sai su ma an ba su manzanci irin wanda aka ba wa Manzanin Allah. Sai Allah ya mayar musu da martani da cewa, shi ya fi sanin inda ya dace ya ajiye manzancinsa, da wanda ya cancanta ya aiko a matsayin manzo ga mutane. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ƙaskanci da wulaƙanci da azabar Allah mai tsanani za su auka wa masu waɗannan laifukan saboda makircin da suka riƙa ƙulla wa Musulmi da Musulunci.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya nufe shi da shiriya, to zai buɗa masa ƙirjinsa ya karɓi Musulunci, wanda kuma ya nufe shi da ɓata, to zai sanya ƙirjinsa ya ƙuntata, hasken imani ya ƙi shigar sa. Misalinsa kamar misalin wanda zai matsa wa kansa hawa sama amma ya kasa domin ba zai iya ba, sai dai ya yi ta numfashi sama-sama kamar ransa zai fita. To kamar haka ne Allah yake ɗora Shaiɗan a kan wanda ya ƙi karɓar gaskiya, ya ɓatar da shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, duk abin da ya bayyana masa a cikin wannan Surar da sauran surorin Alƙur’ani, shi ne abin da ya riga ya zama addininsa, kuma miƙaƙƙiyar hanya wadda zai bi shi da mabiyansa, kuma Allah ya yi bayanin hujjojinsa daki-daki, masu nuna gaskiyar Musulunci ga mutane masu wa’azantuwa, kuma su ne suke da gidan aminci, wato gidan Aljanna a wajen Ubangijinsu, domin shi ne majiɓincin al’amuransu saboda abin da suka kasance suna aikatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saƙon Annabi (ﷺ) ya shafi aljannu kamar yadda ya shafi mutane, su ma kuma suna da sakamako na Aljanna ko na wuta a kansu gwargwadon ayyukansu.

2. Shaiɗanun aljannu suna ɓatar da yawancin mutane ta hanyar yaudarar su da ƙaryar biya musu buƙatunsu na rayuwa.

3. Masu yin mu'amala da aljannu sukan biya wa aljannun buƙatunsu na girmama su da bauta musu da bin umarninsu na saɓon Allah, su kuma sai su daɗaɗa musu ta hanyar hidimta musu da biya musu wasu buƙatunsu na duniya.

4. Idan mutane suka zama azzalumai macuta, to sai Allah ya ɗora musu shuwagabanni azzalumai irinsu su yi ta gana musu azaba. Wannan sunna ce ta Allah a cikin halittarsa.

5. Kafirai a lahira za su yi shaida iri biyu a kan kawunansu. Ta farko, shaidar manzannin Allah sun je musu, ta biyu, shaidar cewa sun kafirce musu.

6. Allah ba ya kama bayinsa da laifi sai ya aiko musu da manzo sun bijire masa.

Suratul An'am (128-131)

وَيَوْمَ يَحْشُرُهُمْ جَمِيعًا يَٰمَعْشَرَ ٱلْجِنِّ قَدِ ٱسْتَكْثَرْتُم مِّنَ ٱلْإِنسِ ۖ وَقَالَ أَوْلِيَآؤُهُم مِّنَ ٱلْإِنسِ رَبَّنَا ٱسْتَمْتَعَ بَعْضُنَا بِبَعْضٍ وَبَلَغْنَآ أَجَلَنَا ٱلَّذِىٓ أَجَّلْتَ لَنَا ۚ قَالَ ٱلنَّارُ مَثْوَىٰكُمْ خَٰلِدِينَ فِيهَآ إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُ ۗ إِنَّ رَبَّكَ حَكِيمٌ عَلِيمٌ ﴿١٢٨﴾ وَكَذَٰلِكَ نُوَلِّى بَعْضَ ٱلظَّٰلِمِينَ بَعْضًۢا بِمَا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ﴿١٢٩﴾ يَٰمَعْشَرَ ٱلْجِنِّ وَٱلْإِنسِ أَلَمْ يَأْتِكُمْ رُسُلٌ مِّنكُمْ يَقُصُّونَ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتِى وَيُنذِرُونَكُمْ لِقَآءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَا ۚ قَالُوا۟ شَهِدْنَا عَلَىٰٓ أَنفُسِنَا ۖ وَغَرَّتْهُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا وَشَهِدُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ أَنَّهُمْ كَانُوا۟ كَٰفِرِينَ ﴿١٣٠﴾ ذَٰلِكَ أَن لَّمْ يَكُن رَّبُّكَ مُهْلِكَ ٱلْقُرَىٰ بِظُلْمٍ وَأَهْلُهَا غَٰفِلُونَ ﴿١٣١﴾

128. Kuma (ka tuna) ranar da zai tara su gaba ɗaya (Ya ce): "Ya ku jama'ar aljannu, haƙiƙa kun samu mabiya da yawa daga cikin mutane." Sai majiɓinta lamarinsu cikin mutane su ce: "Ya Ubangijinmu; mun dai daɗaɗa wa junanmu kuma mun kawo ƙarshen lokacin da Ka yanka mana." Sai Ya ce: "Wuta ita ce makomarku, za ku dawwama a cikinta, sai dai abin da Allah Ya ga dama." Lalle Ubangijinka Mai hikima ne, Mai yawan sani.

129. Kuma kamar haka ne Muke ɗora wani sashi na azzalumai a kan wani sashi, saboda abin da suka kasance suna aikatawa.

130. Ya ku jama'ar aljannu da mutane, shin manzanni daga cikinku ba su zo muku ba, suna karanta muku ayoyina, kuma suna gargaɗin ku game da saduwarku da wannan yini?" Sai su ce: "Mun ba da shaida a kan kawunanmu;" rayuwar duniya kuma ta ruɗe su, kuma suka yi wa kansu shaidar cewa lalle su sun kasance kafirai.

131. Haka ta faru ne, saboda Ubangijinka bai zamanto Mai hallakar da wata alƙarya saboda kafircewarta ba, alhali mutanenta suna cikin gafala.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da Annabi (ﷺ) ne ranar da zai tattara mushirikai tare da shaiɗanun aljannu iyayen gidansu, sai ya ce wa aljannu: Haƙiƙa sun ɓatar da mutane da yawa. Sai mabiyansu mutane su bayar da amsa suna shaida wa Ubangijinsu cewa, sun dai daɗaɗa wa

junansu ne kawai; aljani ya ji daɗin biyayyar da mutum ya yi masa, shi kuma mutum ya ji daɗin hidimar da aljani ya yi masa da biya masa wasu buƙatunsa na son zuciya, kuma ga shi sun kawo ƙarshen lokacin da aka yanka musu na mutuwa ko na zaman duniya. Sai Allah ya tabbatar musu cewa, wuta ce makomarsu ta har abada, sai dai abin da Allah ya ga dama, kamar fitar da waɗanda laifinsu bai kai ga kafirci ba. Lalle Allah Ubangiji mai hikima ne a cikin duk ayyukansa, kuma masani ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda ya ɗora wasu shaiɗanun aljannu a kan wasu karkatattun mutane suka ɓatar da su, to hakanan yake ɗora wasu azzalumai a kan wasu su yi ta gallaza musu azaba iri-iri ba yadda suka iya, saboda irin abin da suka kasance suna aikatawa na zalunci da saɓa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, a ranar alƙiyama zai kira taron aljannu da na mutane, ya tambaye su cewa, shin manzanni daga cikinsu ba su je musu suna karanta musu ayoyinsa ba, kuma suna gargaɗin su game da saduwarsu da wannan rana? Sai su tabbatar masa da cewa, lalle waɗannan manzanni sun je musu, kuma sun faɗa musu gaskiya, to amma sai suka ƙi yarda, suka ƙaryata su. Allah ya bayyana cewa, rayuwar duniya ce ta ruɗe su har suka ƙaryata annabawa, to ga su a wannan rana suna bayar da shaida da kansu cewa su kafirai ne masu laifi.
Daga nan sai Allah ya nuna cewa, wannan gargaɗi da tsawatarwa da manzanni suka yi ta yi a duniya ya faru ne domin kada Allah ya halakar da wata ƙasa saboda kafircinta, alhali ba a gargaɗe su an yanke musu hanzari ba ta hanyar aiko musu da wani manzo da hujjoji bayyanannu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alheri da sharri mataki-mataki ne, kafirci da fasiƙanci su ma matakai ne, wani yana sama da wani, kamar yadda imani da kyawawan ayyuka suke matakai, wani ya fi wani.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai iko ne ya halaka duk wanda yake bayan ƙasa, ya halicci wasu mutane na daban, waɗanda za su bambanta da na farko a harsuna da al'adu da wuraren zama.

3. Bautar masu bauta su take amfana, amma shi Allah mawadaci ne a kan komai.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya ƙyale azzalumi komai daɗewa, kuma aikinsa ba ya nasara.

Suratul An'am (132-135)

وَلِكُلّٖ دَرَجَٰتٞ مِّمَّا عَمِلُواْۚ وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا يَعۡمَلُونَ ١٣٢ وَرَبُّكَ ٱلۡغَنِيُّ ذُو ٱلرَّحۡمَةِۚ إِن يَشَأۡ يُذۡهِبۡكُمۡ وَيَسۡتَخۡلِفۡ مِنۢ بَعۡدِكُم مَّا يَشَآءُ كَمَآ أَنشَأَكُم مِّن ذُرِّيَّةِ قَوۡمٍ ءَاخَرِينَ ١٣٣ إِنَّ مَا تُوعَدُونَ لَأٓتٖۖ وَمَآ أَنتُم بِمُعۡجِزِينَ ١٣٤ قُلۡ يَٰقَوۡمِ ٱعۡمَلُواْ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمۡ إِنِّي عَٰمِلٞۖ فَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَ مَن تَكُونُ لَهُۥ عَٰقِبَةُ ٱلدَّارِۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ١٣٥

132. Kuma kowanne yana da nasa matsayi game da abin da suka aikata, kuma Ubangijinka bai zama Mai rafkana ba dangane da abin da suke aikatawa.

133. Kuma Ubangijinka Shi ne Mawadaci, Mai rahama. Idan Ya ga dama sai Ya tafiyar da ku, kuma Ya maye gurbinku da waɗanda Ya ga dama, kamar yadda Ya fare ku daga zurriyar waɗansu mutanen daban.

134. Lalle abin da ake yi Muku alƙawarinsa mai zuwa ne; kuma ku ba za ku iya kuɓucewa (daga azabarmu) ba.

135. Ka ce: “Ya ku mutanena, ku yi aiki a kan irin hanyarku, lalle ni ma mai yin aiki ne (kan hanyata); don haka da sannu za ku san wanda zai yi kyakkyawan ƙarshe. Lalle su dai azzalumai ba za su rabauta ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa mutane suna da matsayi iri daban-daban a lahira, kowa gwargwadon aikinsa, gwargwadon matsayinsa, wanda ya yi aikin alheri ya ga alheri, wanda ya yi mummunan aiki kuma ya ga mummunan sakamako.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa shi mawadaci ne, ba ya buƙata a wurin kowa, shi ne ake da buƙata a wurinsa, kuma mai rahama ne ga bayinsa, yana saka musu da lada fiye da ayyukansu, yana yafe musu laifukansu bai damu ba. Idan ya ga dama yana iya hallaka duk wanda yake a bayan ƙasa, ya halicci wasu mutanen daban waɗanda za su yi masa biyayya, ba za su saɓa masa ba, kamar yadda ya samar da waɗannan mutanen daga zurriyyar wasu mutanen daban.

An karɓo daga Abu Zarri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Annabi (ﷺ) ya ji daga Allah yana cewa: “….ya ku bayina, lalle ku ba ku isa ku cuce ni ba balle ku cutar da ni, kuma ba ku isa ku amfane ni ba, balle har ku amfanar da ni. Ya ku bayina, da a ce na farkonku da na ƙarshenku da mutanenku da aljannunku, za su zama suna da zuciya irin ta wanda ya fi kowa tsoron Allah, wannan ba zai ƙara komai a cikin mulkina ba. Ya ku bayina, da a ce na farkonku da na ƙarshenku da mutanenku da aljannunku, za su zama suna da zuciya irin ta wanda ya fi kowa fajirci, wannan ba zai rage komai daga mulkina ba....” [Muslim #2577].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, azabar da yake yi wa kafirai gargaɗi da ita tana nan tafe babu makawa, kuma su ba za su iya tsere mata ba.
Sannan ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa wa mushirikan Kuraishawa cewa, idan ya yi kiran su kan su yi imani sun ƙi su amsa masa, to su ci gaba da aikin da suka zaɓar wa kansu, shi ma zai ci gaba da bin umarnin Ubangijinsa; lokacin da azaba ta zo musu za su gane wane ne yake kan hanyar shiriya, wanda kuma zai yi kyakkyawan ƙarshe a duniya da lahira, muminai ne ko kafirai? Haƙiƙa su dai azzalumai ba sa rabauta duniya da lahira.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash’ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Lalle Allah yana jinkirta wa azzalumi, amma duk sa’adda ya damƙe shi, to ba zai iya kuɓuce masa ba.” Sai Annabi (ﷺ) ya karanta faɗar Allah: “Haka kuwa damƙar Ubangijinka take, idan ya damƙi alƙaryu yayin da suka yi zalunci, lalle damƙarsa mai raɗaɗi ce mai tsanani.” [Bukhari #4686].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bai halatta a bauta wa Allah da wani abu ba sai wanda ya shar’anta da nassin Alƙur’ani ko sunnar Annabi (ﷺ).

2. Shaiɗanu ne suke ƙawata wa mai laifi aikin laifinsa har ya zamanto ba ya ganin muninsa ko cutar da ke tattare da shi. Da a ce mai laifi ya haƙiƙance cutar da laifinsa zai jawo masa, to da ya nisance shi.

3. Duk wanda ya yi biyayya ga wanin Allah wajen tsara masa shari’ar da ta saɓa wa shari’ar Allah, to ya haɗa Allah da wani.

وَجَعَلُواْ لِلَّهِ مِمَّا ذَرَأَ مِنَ ٱلۡحَرۡثِ وَٱلۡأَنۡعَٰمِ نَصِيبٗا فَقَالُواْ هَٰذَا لِلَّهِ بِزَعۡمِهِمۡ وَهَٰذَا لِشُرَكَآئِنَاۖ فَمَا كَانَ لِشُرَكَآئِهِمۡ فَلَا يَصِلُ إِلَى ٱللَّهِۖ وَمَا كَانَ لِلَّهِ فَهُوَ يَصِلُ إِلَىٰ شُرَكَآئِهِمۡۗ سَآءَ مَا يَحۡكُمُونَ ١٣٦ وَكَذَٰلِكَ زَيَّنَ لِكَثِيرٖ مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ قَتۡلَ أَوۡلَٰدِهِمۡ شُرَكَآؤُهُمۡ لِيُرۡدُوهُمۡ وَلِيَلۡبِسُواْ عَلَيۡهِمۡ دِينَهُمۡۖ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَا فَعَلُوهُۖ فَذَرۡهُمۡ وَمَا يَفۡتَرُونَ ١٣٧ وَقَالُواْ هَٰذِهِۦٓ أَنۡعَٰمٞ وَحَرۡثٌ حِجۡرٞ لَّا يَطۡعَمُهَآ إِلَّا مَن نَّشَآءُ بِزَعۡمِهِمۡ وَأَنۡعَٰمٌ حُرِّمَتۡ ظُهُورُهَا وَأَنۡعَٰمٞ لَّا يَذۡكُرُونَ ٱسۡمَ ٱللَّهِ عَلَيۡهَا ٱفۡتِرَآءً عَلَيۡهِۚ سَيَجۡزِيهِم بِمَا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ ١٣٨ وَقَالُواْ مَا فِي بُطُونِ هَٰذِهِ ٱلۡأَنۡعَٰمِ خَالِصَةٞ لِّذُكُورِنَا وَمُحَرَّمٌ عَلَىٰٓ أَزۡوَٰجِنَاۖ وَإِن يَكُن مَّيۡتَةٗ فَهُمۡ فِيهِ شُرَكَآءُۚ سَيَجۡزِيهِمۡ وَصۡفَهُمۡۚ إِنَّهُۥ حَكِيمٌ عَلِيمٞ ١٣٩ قَدۡ خَسِرَ ٱلَّذِينَ قَتَلُوٓاْ أَوۡلَٰدَهُمۡ سَفَهَۢا بِغَيۡرِ عِلۡمٖ وَحَرَّمُواْ مَا رَزَقَهُمُ ٱللَّهُ ٱفۡتِرَآءً عَلَى ٱللَّهِۚ قَدۡ ضَلُّواْ وَمَا كَانُواْ مُهۡتَدِينَ ١٤٠

136. Kuma sun sanya wa Allah wani kaso cikin abin da Ya halitta na amfanin gona da dabbobin gida, sai suka riƙa cewa: “Wannan kaso na Allah ne”, a riyawarsu, “Wannan kuma na gumakanmu ne;” sannan abin da ya kasance na gumakansu ba zai isa ga Allah ba; abin da kuwa ya kasance na Allah, to shi zai isa ga gumakansu. Abin da suke hukuntawa ya munana.

137. Kuma kamar haka ne abokan tarayyarsu suka ƙawata wa yawancin mushirikai su dinga kashe ‘ya’yansu, don su hallakar da su, kuma don su rikita musu addininsu. Kuma da Allah Ya ga dama da ba su aikata haka ba. To ka ƙyale su da irin abin da suke ƙagawa.

138. Kuma suka ce: “Waɗannan dabbobi na gida da kuma amfanin gona haramtattu ne, ba wanda zai ci su sai wanda muka ga dama,” a riyawarsu. Waɗansu dabbobin kuma an haramta hawansu, waɗansu dabbobin kuma ba sa ambaton sunan Allah a kansu (yayin yankan su), don kawai su yi masa ƙage. Da sannu zai yi musu sakamakon abin da suka kasance suna ƙagawa.

139. Kuma suka ce: “Abin da yake cikin waɗannan dabbobi, a keɓance yake ga mazajenmu, amma haramun ne ga matayenmu.” Idan kuma ya zamo mushe, to su duka sai su yi tarayya a kansa. Da sannu (Allah) zai yi musu sakayyar wannan abin da suka siffanta. Lalle Shi Mai hikima ne, Mai yawan sani.

140. Haƙiƙa waɗannan da suka kashe ‘ya’yansu don wauta, ba tare da ilimi ba sun taɓe, kuma suka haramta wa kansu abin da Allah Ya arzuta su da shi, don ƙage ga Allah. Haƙiƙa sun ɓata, kuma ba su kasance shiryayyu ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin irin rashin hankali da wautar da mushirikan Larabawa suka riƙa yi a lokacin jahiliyya kafin zuwan Musulunci. Watau amfanin gona da suka noma da dabbobinsu sukan kasa shi kaso biyu, kaso ɗaya su ce na Allah ne, kaso na biyu kuwa su ce na gumakansu, duk kuwa da cewa gaba ɗayansu Allah ne ya halicce su. Sannan kuma idan wani kason da suka ware wa gumakansu ya shiga cikin kason Allah, to sai su dawo da shi wurinsa, amma idan kason da suka ware wa Allah ya gauraya a cikin kason gumakansu, to ba za su dawo da shi wurinsa ba, sai su bar shi ba tare da sun damu ba. Wannan hukunci nasu kuwa ya yi muni.
Hakanan shaiɗanun da suke bauta wa ba Allah ba sun ƙawata musu su riƙa kashe ‘ya’yansu, don su hallaka su, su rikirkita musu addininsu. Da kuwa Allah ya ga dama da ya hana su irin wannan ɗanyen aiki, to sai dai bisa hikimarsa ya ƙyale su suna ta biyayya ga shaiɗanunsu suna ci gaba da kashe ‘ya’yansu. Sai Allah ya umarci Annabi (ﷺ) ya rabu da su da irin ƙarairayin da suke ƙagawa suna jingina wa Allah, ba za su cuce shi da komai ba.

Wata katoɓarar kuma ta mushirikai ita ce, sai su ware wasu dabbobi da wani amfanin gona su ce wannan haramun ne wani ya ci su, sai wanda suka ga dama suka yi wa izini. Suna yin haka kuwa ba tare da wata hujja ko madogara ba sai dai ƙarya kawai. Hakanan kuma suna ware wasu dabbobi su haramta a hau su; wasu kuma ba za su ambaci sunan Allah a kansu ba, don haka ba za a yi hajji a kansu ba, hakanan idan an hau su ko an zo tatsar nononsu ko za a yanka su, to ba za a kira sunan Allah ba. Sai Allah ya ce, zai saka musu a kan abin da suka kasance suna ƙirƙira.
Wata ƙaryar kuma ita ce, mushirikai sukan ware wasu dabbobi su ce maza ne kaɗai ya halatta su ci abin da za su haifa ko su sha nononsu, amma wannan haramun ne ga mata. Amma kuma idan abin da suka haifa bai zo da rai ba ko ya mutu bayan an haife shi, to wannan maza da mata za su yi tarayya wajen cin namansa. Sai Allah ya bayyana cewa, zai saka wa masu yi masa ƙarya suna haramta abin da ya halatta, su halatta abin da ya haramta. Lalle kuma Allah masani ne mai hikima.Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mushirikai masu kashe ‘ya’yansu don wauta da rashin hankali da rashin ilimi, suna haramta abin da Allah ya arzuta su da shi don ƙaga masa ƙarya, waɗannan sun yi muguwar asara, kuma sun kauce wa hanyar shiriya, ba su yi sa’ar dace da ita ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tunatar da mutane ni’imomin da Allah ya yi musu domin su gode masa ta hanyar bin umarninsa da guje wa haninsa.

2. Duba zuwa ga abubuwan da Allah yake halitta a cikin gonakinmu na bishiyoyi da shuke-shuke iri daban-daban masu saɓani da juna da masu kama da juna a zahiri, masu saɓani wajen ɗanɗano, lalle za mu fahimci akwai mahaliccinsu Ɗaya tilo wanda ya zuba tsarinsu kamar yadda muke gani, domin ba su suka yi kansu ba.

3. Kula da kai yana gaba da kula da wani, shi ya sa Allah ya gabatar da umarnin masu gona su ci daga kayan amfanin gonarsu, sannan su fitar da haƙƙin masu haƙƙi daga ciki.

Suratul An’am (141-142)

*وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَ جَنَّٰتٍ مَّعۡرُوشَٰتٍ وَغَيۡرَ مَعۡرُوشَٰتٍ وَٱلنَّخۡلَ وَٱلزَّرۡعَ مُخۡتَلِفًا أُكُلُهُۥ وَٱلزَّيۡتُونَ وَٱلرُّمَّانَ مُتَشَٰبِهًا وَغَيۡرَ مُتَشَٰبِهٍۚ كُلُواْ مِن ثَمَرِهِۦٓ إِذَآ أَثۡمَرَ وَءَاتُواْ حَقَّهُۥ يَوۡمَ حَصَادِهِۦۖ وَلَا تُسۡرِفُوٓاْۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُسۡرِفِينَ ١٤١ وَمِنَ ٱلۡأَنۡعَٰمِ حَمُولَةً وَفَرۡشٗاۚ كُلُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ وَلَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ١٤٢

141. Kuma Shi ne Wanda Ya halicci lambuna waɗanda suke da tsirrai masu yaɗo da marasa yaɗo da kuma dabino da shukoki waɗanda suka sha bamban da juna wajen ɗanɗanonsu, da kuma zaitun da ruman, mai kama da juna, da wanda ba ya kama da juna. Ku ci daga ‘ya’yansa, idan ya yi ‘ya’ya, kuma ku bayar da zakkarsa a ranar girbinsa, kuma kada ku yi almubazzaranci. Lalle Shi (Allah) ba Ya son masu almubazzaranci.

142. Daga cikin dabbobin gida kuma akwai masu ɗaukan kaya da kuma ƙanana. Ku ci daga abin da Allah Ya arzuta ku da shi, kuma kada ku bi hanyoyin Shaiɗan. Lalle shi maƙiyi ne mai bayyana ƙiyayya a gare ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin abubuwan da ya samar wa ɗan’adam na gonaki da lambuna waɗanda suke cike da itatuwa da shuke-shuke iri-iri masu ‘ya’ya da ganyayyaki

daban-daban. Daga cikinsu akwai masu yaɗo suna bin ƙasa ko shinge da waɗanda suke tsaye a kan itatuwansu. Hakanan ya halicci itatuwan dabino da shuke-shuke mabambanta ɗanɗano da kuma zaitun da rumman waɗanda ganyayyakinsu suke kama da juna amma ‘ya’yansu da ɗanɗanonsu suka sha bamban. Allah ya umarci bayinsa da su ci ‘ya’yan itatuwansu idan sun yi ‘ya’ya, kuma su fitar da zakkarsu a ranar girbi, ya kuma hana su yin almubazzaranci domin shi ba ya son masu almubazzaranci da abinci ko dukiya.
Da farko an umarci manoma da su ba da haƙƙin amfanin gonarsu ba tare da bayanin gwargwadon abin da za su fitar ba, sai daga baya ne shari’a ta yi bayanin gwargwadon abin da za a fitar na zakkar amfanin gona, wanda shi ne kaso ɗaya cikin goma (ushuri), idan noman damina ne, ko kaso ɗaya ciki ashirin (rabin ushuri), idan noman rani ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi ne ya halicci dabbobi masu ɗaukar kaya da mutane, kamar raƙuma da shanu da ƙananan dabbobi, ya kuma umarce su da su ci daga abin da ya arzuta su da shi, ya halatta musu cin sa. Ya kuma hana su bin hanyoyin Shaiɗan domin shi Shaiɗan maƙiyinsu ne na sarari.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dabbobin da Allah ya halatta wa ɗan’adam cin namansu da hawansu wajen tafiye-tafiyensa da ɗora musu kaya, wata ni’ima ce ga mutane da ya wajaba su yi wa Allah godiya a kanta.

2. Bai halatta ga Musulmi ya haramta cin naman wata dabba da Allah ya halatta cin ta ba; yin haka aiki ne na mushirikai.

3. Mafi girman zalunci shi ne yi wa Allah ƙarya ta hanyar ƙirƙiro wasu abubuwa da sunan addini da sanya su cikin shari’ar Allah ba tare da wani dalili na ilimi ba sai don cim ma wata buƙata ko ɓatar da mutane.

Suratul An’am (143-144)
ثَمَٰنِيَةَ أَزۡوَٰجٖۖ مِّنَ ٱلضَّأۡنِ ٱثۡنَيۡنِ وَمِنَ ٱلۡمَعۡزِ ٱثۡنَيۡنِۗ قُلۡ ءَآلذَّكَرَيۡنِ حَرَّمَ أَمِ ٱلۡأُنثَيَيۡنِ أَمَّا ٱشۡتَمَلَتۡ عَلَيۡهِ أَرۡحَامُ ٱلۡأُنثَيَيۡنِۖ نَبِّـُٔونِي بِعِلۡمٍ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ١٤٣ وَمِنَ ٱلۡإِبِلِ ٱثۡنَيۡنِ وَمِنَ ٱلۡبَقَرِ ٱثۡنَيۡنِۗ قُلۡ ءَآلذَّكَرَيۡنِ حَرَّمَ أَمِ ٱلۡأُنثَيَيۡنِ أَمَّا ٱشۡتَمَلَتۡ عَلَيۡهِ أَرۡحَامُ ٱلۡأُنثَيَيۡنِۖ أَمۡ كُنتُمۡ شُهَدَآءَ إِذۡ وَصَّىٰكُمُ ٱللَّهُ بِهَٰذَاۚ فَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبٗا لِّيُضِلَّ ٱلنَّاسَ بِغَيۡرِ عِلۡمٍۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٤٤

143. (Dabbobin) nau’i takwas ne, daga tumaki akwai jinsi biyu, haka kuma daga awaki akwai jinsi biyu. Ka ce: “Shin mazan biyu ne Ya haramta ko kuma matan biyu ko kuma abin da yake cikin mahaifar matan biyu? Ku ba ni labari da ilimi in kun kasance ku masu gaskiya ne.”

144. Haka kuma raƙuma akwai jinsi biyu, daga cikin shanu ma akwai jinsi biyu. Ka ce: “Shin mazan guda biyu Ya haramta ko matan biyu ko kuma abin da yake cikin mahaifar matan biyu ya haramta ko kuma kun zama shaidu yayin da Allah Ya yi muku wasicci da wannan abin?” To ba wanda ya fi zaluntar kansa fiye da wanda ya ƙirƙiri ƙarya, ya jingina wa Allah don ya ɓatar da mutane ba tare da ilimi ba. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin nau’ukan dabbobin da ya halatta cin namansu su takwas: Akwai tumakai guda biyu, wato rago da tinkiya, akwai kuma awaki su ma guda biyu, wato akuya da taure. Allah ya umarci Annabi Muhammad (ﷺ) ya tambayi kafirai masu haramta cin naman wasu keɓatattun dabbobi ko hawan su da ɗora musu kaya ko hana mata cin naman wasu

dabbobi sai maza kaɗai ko hana mata cin naman ‘ya’yan da waɗannan dabbobi suka haifa, sai dai idan ba su zo da rai ba ko sun mutu bayan haihuwa, ya tambaye su wane jinsi ne Allah ya haramta a cikinsu, jinsin maza ko na mata ko abin da cikkunan matan suka ƙunsa? Ba ɗaya daga cikin waɗannan kashe-kashe da zai zama amsarsu. Don haka sai ya umarce shi da ya sa su kawo wani labari na gaskiya da ilimi a kan bambancin da ke tsakanin dabbobin da suka haramta da kuma waɗanda suka halatta, idan har sun kasance su masu gaskiya ne a ɗa’awarsu da ƙaryar da suke jingina wa Allah da ƙage.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci sauran nau’ukan dabbobin guda huɗu, su ne raƙuma, wato raƙumi da taguwa, sai shanu, wato sa da saniya, su ma ya umarci Annabi (ﷺ) ya sake maimaita musu irin waccan tambayar domin su faɗa masa bambanci tsakanin dabbobin da suka haramta da waɗanda suka halatta. To idan ba su da amsar da za su bayar, me ya sa suka haramta wasu suka halatta wasu? Ko sun halarci wurin da Allah ya tara su ya yi musu wasiyya da hakan? Wannan ma bai faru ba. To daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu babban azzalumi kamar wanda yake yi wa Allah ƙarya don kawai ya ɓatar da mutane ba da wani ilimi ba. To haƙiƙa Allah ba ya shiryar da mutane azzalumai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu wani mai haƙƙin haramtawa sai ta hanyar wahayi.

2. Cin naman mushe shi aka haramta, amma ana iya amfani da fatarsa bayan an jeme ta.

3. Jini mai kwarara ne aka haramta banda wanda ya shiga cikin jijiyoyi ko ya daskare a jikin nama.

4. An haramta cin duk wani abu da aka yanka da sunan wani ba Allah ba, ko da kuwa dabbar da aka halatta ce.

5. An halatta wa mai larura ya ci abin da aka haramta cin sa, amma gwargwadon yadda zai magance lalurarsa ba tare da zaƙewa ba.

6. Zalunci yana jawo uƙubar Allah, kamar yadda ya faru ga Yahudawa.

7. Rahamar Allah mayalwaciya ce, amma kada hakan ya ruɗi mai sabon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da saɓonsa ya ƙi tuba; wannan idan azabar Allah ta zo masa babu mai kare shi.

Suratul An’am (145-147)

قُل لَّآ أَجِدُ فِي مَآ أُوحِيَ إِلَيَّ مُحَرَّمًا عَلَىٰ طَاعِمٖ يَطۡعَمُهُۥٓ إِلَّآ أَن يَكُونَ مَيۡتَةً أَوۡ دَمٗا مَّسۡفُوحًا أَوۡ لَحۡمَ خِنزِيرٖ فَإِنَّهُۥ رِجۡسٌ أَوۡ فِسۡقًا أُهِلَّ لِغَيۡرِ ٱللَّهِ بِهِۦۚ فَمَنِ ٱضۡطُرَّ غَيۡرَ بَاغٖ وَلَا عَادٖ فَإِنَّ رَبَّكَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٤٥ وَعَلَى ٱلَّذِينَ هَادُواْ حَرَّمۡنَا كُلَّ ذِي ظُفُرٖۖ وَمِنَ ٱلۡبَقَرِ وَٱلۡغَنَمِ حَرَّمۡنَا عَلَيۡهِمۡ شُحُومَهُمَآ إِلَّا مَا حَمَلَتۡ ظُهُورُهُمَآ أَوِ ٱلۡحَوَايَآ أَوۡ مَا ٱخۡتَلَطَ بِعَظۡمٖۚ ذَٰلِكَ جَزَيۡنَٰهُم بِبَغۡيِهِمۡۖ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ١٤٦ فَإِن كَذَّبُوكَ فَقُل رَّبُّكُمۡ ذُو رَحۡمَةٖ وَٰسِعَةٖ وَلَا يُرَدُّ بَأۡسُهُۥ عَنِ ٱلۡقَوۡمِ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ١٤٧

145. Ka ce: “Daga cikin abin da aka saukar mini na manzanci ban samu wani abinci da aka haramta cinsa ba, sai fa idan ya zamo mushe ne ko jini mai kwarara, ko kuma naman alade, to lalle wannan ƙazanta ne, ko kuma abin da ya zamo fasiƙanci ne wanda aka yanka shi ba da sunan Allah ba.” Sannan wanda ya

matsu, ba tare da shisshigi ba, kuma ba yana mai ƙetare iyaka ba, to lalle Ubangijinka Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

146. Kuma Mun haramta wa Yahudawa duk wata dabba mai kofato; daga shanu da tumaki kuwa Mun haramta musu kitsensu, sai abin da gadon bayansu yake ɗauke da shi ko kayan cikinsu ko abin da ya cakuɗu da ƙashi. Wannan Mun Yi musu sakamako da shi ne saboda zaluncinsu; kuma lalle Mu tabbas Masu gaskiya ne.

147. Sannan idan sun ƙaryata ka, to ka ce: “Ubangijinku Ma’abocin rahama mayalwaciya ne . Kuma ba a iya mayar da azabarsa daga mutanen da suke masu laifi.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa waɗannan kafirai masu haramta abin da Allah ya arzuta su da shi cewa, shi dai bai ga wani abu da Allah ya haramta masa cin sa ba daga cikin abubuwan da suke haramtawa, sai guda huɗu, watau mushe da jini mai kwarara da naman alade, waɗannan ukun ƙazanta ce kuma najasa; na huɗu shi ne abin da aka yanka da sunan wanin Allah; shi kuma wannan saɓon Allah ne. To amma duk wanda ya shiga halin matsuwa, ya rasa abinci sai ɗayan waɗannan abubuwa da aka haramta, to sai ya ci ba da niyyar morewa ba ko barin halal zuwa haram; to lalle Allah mai gafara ne mai jin ƙai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata uƙubar da ya yi wa Yahudawa saboda yawan laifukansu, watau ya haramta musu cin naman duk wata dabba mai farata, da kitsen shanu da tumaki, sai dai kitsen dake gadon bayan waɗannan dabbobi ko wanda yake tare da kayan ciki, ko wanda yake haɗe da ƙashi, kamar kitsen naman cinya. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu wannan uƙubar ce saboda kafircinsu da zaluncinsu, kuma lalle shi Allah tabbas mai gaskiya ne a duk maganganunsa da ayyukansa da hukunce-hukuncensa.

Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Annabinsa cewa, idan kafirai sun ƙaryata shi, to su sani Ubangijinsu mai yalwatacciyar rahama ne ga wanda ya bi shi, don haka su yi gaggawa wajen neman rahamarsa, su aikata abin da yake umartar su da shi, su bar abin da yake hana su. Yana daga cikin rahamarsa jinkirtawar da yake yi musu, ba ya gaggauto musu da azabarsa, to amma su sani idan har azabarsa ta zo, babu mai hana ta sauka a kan mutane masu laifi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar mu’ujizar Annabi (ﷺ). Yayin da ya ba da labarin cewa mushirikai za su yi wata magana da ta danganci kare kansu daga shirka da haramta abin da Allah bai haramta ba, kuma sai ga shi sun yi maganar kamar yadda aya ta 35 cikin 'Suratun *Nahli*’ ta nuna.

2. Wajibi ne a kan Musulmi ya tsaya ya yi aiki da shari’a kada ya riƙa kafa hujja da ƙaddara.

3. Sukar masu aiki da zato mai rauni da bin shaci-faɗi maimakon tsayawa a kan bincike na ilimi da dalilai masu ƙarfi.

4. Imani da ranar lahira yana hana ayyukan laifi.

Suratul An’am (148-150)

سَيَقُولُ ٱلَّذِينَ أَشۡرَكُواْ لَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَآ أَشۡرَكۡنَا وَلَآ ءَابَآؤُنَا وَلَا حَرَّمۡنَا مِن شَيۡءٖۚ كَذَٰلِكَ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ حَتَّىٰ ذَاقُواْ بَأۡسَنَاۗ قُلۡ هَلۡ عِندَكُم مِّنۡ عِلۡمٖ فَتُخۡرِجُوهُ لَنَآۖ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَإِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا تَخۡرُصُونَ ١٤٨ قُلۡ فَلِلَّهِ ٱلۡحُجَّةُ ٱلۡبَٰلِغَةُۖ فَلَوۡ شَآءَ لَهَدَىٰكُمۡ أَجۡمَعِينَ ١٤٩ قُلۡ هَلُمَّ شُهَدَآءَكُمُ ٱلَّذِينَ يَشۡهَدُونَ أَنَّ ٱللَّهَ حَرَّمَ هَٰذَاۖ فَإِن شَهِدُواْ فَلَا تَشۡهَدۡ مَعَهُمۡۚ وَلَا تَتَّبِعۡ أَهۡوَآءَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ وَهُم بِرَبِّهِمۡ يَعۡدِلُونَ ١٥٠

148. Waɗanda suke yin shirka za su ce: “Da Allah Ya ga dama, da ba mu yi shirka ba, haka iyayenmu ma da ba su yi ba, kuma da ba mu haramta wani abu ba.” Kamar haka ne waɗanda suka gabace su suka ƙaryata (manzanni), har sai da suka ɗanɗani azabarmu. Ka ce: “Shin kuna da wata hujja ce da za ku fito mana da ita? Ba fa abin da kuke bi sai zato, kuma ku (ba a kan komai kuke ba) face shaci-faɗi.”

149. Ka ce: “To a wurin Allah ne cikakkiyar hujja take; kuma da Ya ga dama, tabbas da Ya shiryar da ku gaba ɗaya.”

150. Ka ce: “Ku kawo shaidunku waɗanda za su ba da shaidar cewa, Allah Shi Ya haramta wannan.” Sannan idan har sun ba da shaidar, to kai kada ka bayar da shaida tare da su. Kuma kada ka bi soye-soyen zukatan waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, waɗanda kuma ba sa yin imani da ranar lahira, su ne kuwa masu daidaita Ubangijinsu (da wani abu).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba mu labarin abin da mushrikai suke cewa, wai da Allah ya ga dama, da su da iyayensu ba za su yi shirka ba, kuma da ba za su haramta komai ba. Kuma tunda har ya ƙyale su suka aikata hakan, wannan a riyawarsu ya nuna cewa ya yarda da abin da suka yi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan bai zama abin mamaki ba, domin hanyar da suka bi ta ƙaryata Annabi (ﷺ) irinta ce dai kafiran da suka gabace su suka bi suka ƙaryata annabawa da ita, har sai da suka ɗanɗani azabar Allah. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tambaye su ko suna da wani ilimi na gaskiya wanda suka dogara da shi mai nuna cewa Allah ya yarda da abin da suke aikatawa? Idan akwai to su fito da wannan ilimin su nuna kowa ya gani. A ƙarshe dai Allah ya tabbatar da cewa, babu wani ilimi da suke da shi in banda zato da shaci-faɗi marar tushe. Ya kuma umarce shi da ya tabbatar musu cewa, Allah ne mai cikakkiyar hujja; da ya ga dama da ya shirye su gaba ɗaya. Kuma Allah ya ce, ya neme su da su zo da shaidunsu wanda zai nuna cewa abubuwan da suka ƙago suna cewa sun haramta Allah ne da kansa ya haramta su. To idan sun kawo shaidun, Allah ya hana Annabi ya yi shaida a kan haka tare da su. Hakanan ya yi masa kashedi da kada ya bi soye-soyen zukatan masu ƙaryata ayoyin Allah waɗanda suka kafirce wa ranar lahira, kuma suka ci gaba da yin shirka da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne a kan malamai su yi wa mutane bayanin abin da Allah ya haramta musu da wanda ya halatta musu ba tare da ɓoye komai ba.

2. Wajibi ne ga mutane, kafin su shiga binciken abubuwan da aka haramta musu da waɗanda aka halatta, su fara sanin haƙƙin Mahaliccinsu Allah na a bauta masa shi kaɗai ba tare da an haɗa shi da wani ba.

3. Kyautata wa iyaye hakki ne mai karfi a kan ‘ya’yansu, shi ya sa aka ambace shi bayan hakkin Allah kai-tsaye.

4. Hakkin iyaye shi ne a yi matukar kyautata musu, amma ba a bauta musu ba, domin bauta hakkin Allah ne shi kadai.

5. Idan bukatar iyaye ta ci karo da hakkin Allah, to hakkin Allah ne za a gabatar.

6. Wajibi ne a kan iyaye su raini ‘ya’yansu, su yi musu kyakkyawar tarbiyya; arzukinsu kuma a hannun Allah yake, a wurinsa za su nema.

7. Dole ne mutum ya guji laifi na sarari da na boye, amma idan ya guje wa na sarari bai guji na boye ba, wannan ya nuna ba don Allah ya bar na sararin ba.

8. Allah (Mai tsarki da daukaka) ba ya dora wa kowane wani rai sai abin da zai iya dauka. Duk abin da ya fi karfin dan’adam to Allah ya yi masa afuwa a kai.

9. Dole ne mumini ya rika yin magana ta gaskiya a wajen yabo ko suka ko bayar da shaida, ba tare da la’akari da kusanci ko soyayya ko kiyayya ba.

10. Kiyaye hakkin masu rauni alama ce ta kafuwar adalci a cikin kowacce al’umma, rashin samun haka wata alama ce ta rushewar wannan al’umma da gushewarta.

Suratul An’am (151-153)

*قُلْ تَعَالَوْاْ أَتْلُ مَا حَرَّمَ رَبُّكُمْ عَلَيْكُمْۖ أَلَّا تُشْرِكُواْ بِهِۦ شَيْـٔٗاۖ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنٗاۖ وَلَا تَقْتُلُوٓاْ أَوْلَٰدَكُم مِّنْ إِمْلَٰقٖ نَّحْنُ نَرْزُقُكُمْ وَإِيَّاهُمْۖ وَلَا تَقْرَبُواْ ٱلْفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنْهَا وَمَا بَطَنَۖ وَلَا تَقْتُلُواْ ٱلنَّفْسَ ٱلَّتِي حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلْحَقِّۚ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ١٥١ وَلَا تَقْرَبُواْ مَالَ ٱلْيَتِيمِ إِلَّا بِٱلَّتِي هِيَ أَحْسَنُ حَتَّىٰ يَبْلُغَ أَشُدَّهُۥۚ وَأَوْفُواْ ٱلْكَيْلَ وَٱلْمِيزَانَ بِٱلْقِسْطِۖ لَا نُكَلِّفُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَاۖ وَإِذَا قُلْتُمْ فَٱعْدِلُواْ وَلَوْ كَانَ ذَا قُرْبَىٰۖ وَبِعَهْدِ ٱللَّهِ أَوْفُواْۚ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَذَكَّرُونَ ١٥٢ وَأَنَّ هَٰذَا صِرَٰطِي مُسْتَقِيمٗا فَٱتَّبِعُوهُۖ وَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلسُّبُلَ فَتَفَرَّقَ بِكُمْ عَن سَبِيلِهِۦۚ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ١٥٣

151. Ka ce: “Ku taho in karanta muku abin da Ubangijinku Ya haramta muku; kada ku hada Shi da wani; kuma ku kyautata wa mahaifa; kuma kar ku kashe ‘ya’yanku saboda talauci; Mu ne za Mu arzuta ku har da su; kuma kada ku kusanci munanan (ayyuka) na sarari da na boye; kuma kada ku kashe ran da Allah Ya haramta (a kashe shi), sai idan da wani hakki. Wannan shi ne abin da (Allah) Ya yi muku wasiyya da shi, don ku zamo masu hankali.

152. “Kuma kada ku kusanci dukiyar maraya sai da kyakkyawar niyya, har sai karfinsa ya kawo; kuma ku cika ma’auni na mudu da na nauyi bisa adalci; ba ma dora wa rai sai abin da zai iya. Kuma idan za ku yi magana to ku yi adalci, ko da kuwa a kan dan’uwa ne na kusa; kuma lalle ku cika alkawarin Allah. Wannan ne abin da (Allah) Yake yi muku wasicci da shi, don ku wa’azantu.”

153. “Kuma lalle wannan shi ne tafarkina mikakke, don haka ku bi shi; kada ku bi wadansu hanyoyi daban, sai su raba ku da hanyarsa. Wannan shi ne abin da (Allah) Yake yi muku wasicci da shi don ku samu takawa.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya nemi mushirikai su taho ya karanta musu gaskiyar abubuwan da Allah ya haramta musu.
Na farko, kada su yi shirka da Allah da komai;
na biyu, su kyautata wa iyaye;
na uku, kada su kashe ‘ya’yansu saboda tsoron talauci; su da `ya`yansu duka Allah shi ne mai azurta su;
na huɗu, kada su kusanci munanan ayyuka na sarari da na ɓoye;
na biyar, kada su kashe ran da Allah ya haramta a kashe shi sai da wani haƙƙi. Waɗannan duka wasiyya ce Allah yake yi musu ko sa hankalta.
Na shida kuma, kada su kusanci dukiyar maraya sai da abin da ya zama maslaha ne a gare shi, har sai ya kawo ƙarfinsa sai su mayar masa da dukiyarsa;
na bakwai, su cika ma’auni na mudu da nauyi bisa adalci, Allah ba ya ɗora wa mutum wani nauyi sai wanda zai iya ɗauka;
na takwas, idan za su yi magana to su faɗi gaskiya ko da ta saɓa wa na kusa da su;
na tara, su cika alƙawarin da ke tsakaninsu da Allah. Wannan wasiyya ce Allah yake yi musu don su wa’azantu.
Wasiyya ta goma kuwa ita ce, wannan addini na Musulunci shi ne miƙaƙƙiyar hanyar Allah, don haka lalle su bi ta kada su bi wasu hanyoyin da suka saɓa mata sai su ɓatar da su daga hanyar Allah. Wannan ita ce wasiyyar da ya yi musu, don su samu taƙawa, watau su kiyaye dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya zana mana wani dogon zane, sai ya ce: “Wannan ita ce hanyar Allah.” Sai kuma ya zana wasu layuka a damansa da hagunsa, sai ya ce: “Waɗannan wasu hanyoyi ne daban-daban, kowacce daga cikinsu akwai Shaiɗan da yake kira zuwa gare ta.” Sai ya karanta wannan ayar ta 153. [Ahmad #4142].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ga Musulmi ya bi Alƙur’ani, ya yi aiki da shi domin shi shiriya ne da rahama.

2. Wajibi ne ga Musulmi ya gaggauta aikin alheri kafin damar yin hakan ta kuɓuce masa.

3. Alƙur’ani littafi ne da ke cike da albarka, don haka duk wanda ya riƙe shi, ya yi aiki da koyarwarsa, rayuwarsa za ta yi albarka duniya da lahira.

4. Shiriyar da take cikin Alƙur’ani ta fi wadda take cikin Attaura da Linjila, shi ya sa zuwan Alƙur’ani ya shafe hukuncin duk wani littafi da ya gabace shi.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana kiran Musulmi da su haɗa kansu a kan littafinsa da sunnar Manzonsa (ﷺ), su guji rarrabuwa ƙungiya-ƙungiya suna faɗa da juna.

6. Duk wanda zai ƙirƙiro bidi’ar da ta saɓa wa sunnar Annabi (ﷺ), to babu ruwan Manzon Allah (ﷺ) da shi da bidi’arsa.

7. Yana daga cikin tabbatacciyar aƙidar Musulmi cewa, a ƙarshen duniya rana za ta fito daga mafaɗarta, yayin da haka ya faru to za a rufe ƙofar karɓar tuba daga masu laifi.

8. Allah ya tabbatar wa da kansa siffar ‘zuwa’, don haka wajibi ne Musulmi ya yarda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai zo a ranar gobe ƙiyama don yi wa bayinsa hisabi.

9. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya karɓar duk wani aiki na ƙwarai sai mai shi yana da imani a zuciyarsa.

Suratul An’am (154-159)

ثُمَّ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ تَمَامًا عَلَى ٱلَّذِيٓ أَحۡسَنَ وَتَفۡصِيلٗا لِّكُلِّ شَيۡءٖ وَهُدٗى وَرَحۡمَةٗ لَّعَلَّهُم بِلِقَآءِ رَبِّهِمۡ يُؤۡمِنُونَ ١٥٤ وَهَٰذَا كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ
مُبَارَكٞ فَٱتَّبِعُوهُ وَٱتَّقُواْ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ١٥٥ أَن تَقُولُوٓاْ إِنَّمَآ أُنزِلَ ٱلۡكِتَٰبُ عَلَىٰ طَآئِفَتَيۡنِ مِن قَبۡلِنَا وَإِن كُنَّا عَن دِرَاسَتِهِمۡ لَغَٰفِلِينَ ١٥٦ أَوۡ
تَقُولُواْ لَوۡ أَنَّآ أُنزِلَ عَلَيۡنَا ٱلۡكِتَٰبُ لَكُنَّآ أَهۡدَىٰ مِنۡهُمۡۚ فَقَدۡ جَآءَكُم بَيِّنَةٞ مِّن رَّبِّكُمۡ وَهُدٗى وَرَحۡمَةٞۚ فَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّن كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
وَصَدَفَ عَنۡهَاۗ سَنَجۡزِي ٱلَّذِينَ يَصۡدِفُونَ عَنۡ ءَايَٰتِنَا سُوٓءَ ٱلۡعَذَابِ بِمَا كَانُواْ يَصۡدِفُونَ ١٥٧ هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن تَأۡتِيَهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَوۡ يَأۡتِيَ
رَبُّكَ أَوۡ يَأۡتِيَ بَعۡضُ ءَايَٰتِ رَبِّكَۗ يَوۡمَ يَأۡتِي بَعۡضُ ءَايَٰتِ رَبِّكَ لَا يَنفَعُ نَفۡسًا إِيمَٰنُهَا لَمۡ تَكُنۡ ءَامَنَتۡ مِن قَبۡلُ أَوۡ كَسَبَتۡ فِيٓ إِيمَٰنِهَا خَيۡرٗاۗ
قُلِ ٱنتَظِرُوٓاْ إِنَّا مُنتَظِرُونَ ١٥٨ إِنَّ ٱلَّذِينَ فَرَّقُواْ دِينَهُمۡ وَكَانُواْ شِيَعٗا لَّسۡتَ مِنۡهُمۡ فِي شَيۡءٍۚ إِنَّمَآ أَمۡرُهُمۡ إِلَى ٱللَّهِ ثُمَّ يُنَبِّئُهُم بِمَا كَانُواْ يَفۡعَلُونَ ١٥٩

154. Sannan Muka bai wa Musa littafin (Attaura) don cika (ni’imarmu) ga wanda ya kyautata, kuma bayani ne na kowane irin abu, kuma shiriya ne da rahama, domin su zamo masu imani da haɗuwa da Ubangijinsu.

155. Kuma wannan Littafi (Alƙur’ani) Mun saukar da shi, yana mai cike da albarka, don haka ku bi shi, kuma ku kiyaye dokokin (Allah), domin a ji ƙan ku.

156. Don kada ku ce: “Kungiya biyu ne waɗanda suka gabace mu kawai aka saukar wa da Littafi, mu kuma ba mu san komai game da abin da suka karanta ba.”

157. Ko kuma ku ce: “In da mu aka saukar wa da littafin, to da lalle mun fi su shiryuwa.” To ai haƙiƙa hujja ta riga ta zo muku daga Ubangijinku, da kuma shiriya da rahama; don haka babu wanda ya fi zalunci fiye da wanda ya ƙaryata ayoyin Allah, kuma ya yi watsi da su. Da sannu za Mu saka wa waɗanda suke bijire wa ayoyinmu da mummunar azaba, saboda bijirewar da suke yi.

158. Sannan ba abin da suke sauraro face mala’iku su zo musu ko Ubangijinka Ya zo musu ko wani sashi na ayoyin Ubangijinka su zo. Ranar da wasu daga ayoyin Ubangijinka za su zo, to babu wani rai da imaninsa zai yi amfani, idan a da can bai yi imani ba ko bai yi aikin alheri ba cikin imaninsa. Ka ce: “Ku jira, mu ma masu jira ne.”

159. Lalle waɗanda suka rarraba addininsu kuma suka kasance ƙungiya-ƙungiya, to ba ruwanka da su. Al’amarinsu yana ga Allah ne kawai, sannan zai ba su labarin abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin cewa, ya ba wa Annabi Musa littafin Attaura wanda ya ƙunshi duk abubuwan da za a buƙata na shari’a a lokacinsa, ya kuma yi masa wannan tagomashi ne sakamakon ayyukansa na kirki, don kuma ya cika masa ni’imominsa, kuma ya yi masa bayanin komai da al’ummarsa suke buƙatar sani na addini da rayuwa filla-filla, kuma ya zamanto shiriya da rahama gare su, sannan kuma su yi imani da saduwa da Ubangijinsu ranar alƙiyama.
Kuma ya yi bayanin cewa, ya saukar da wannan Alƙur’ani mai cike da albarka da alheri da ilimi mai tarin yawa, ya kuma umarci bayi su bi shi, kuma su kiyaye dokokinsa don su samu a yi musu rahama.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya saukar da shi wannan Alƙur’ani ne don ya yanke wa mushirikai duk wani hanzari da wata hujja da za su iya fakewa da ita, wato su ce an saukar

da littafi ne ga al'ummomi biyu da suka gabace su, su ne Yahudawa da Nasara, kuma su ba su da wata masaniya da waɗannan al'ummomin, kuma ba sa fahimtar harshen da aka saukar da littafin da shi, kuma babu wani umarni a cikinsa da ya shafe su.
Hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar musu da Alƙur'ani don a yanke abin da za su iya kafa hujja da shi, ta cewa da su ne aka saukar wa da littafi kamar yadda aka saukar wa Yahudawa da Nasara, da sun zama shiryayyu fiye da su. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, Alƙur'ani ya zo musu da hujja bayyananniya da shiriya da rahama a gare su. Ya bayyana cewa, babu babban azzalumi kamar wanda ya ƙaryata ayoyin Allah, ya bijire musu bayan sun zo masa. Sai Allah ya yi alƙawarin narko mai tsanani na azaba ga waɗanda suke bijire wa ayoyinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da ma babu abin da mushirikai suke sauraro sai kawai su ga mala'iku sun zo karɓar rayukansu suna kafirai, ko Ubangiji ya zo musu su gan shi da idonsu ko kuma wasu ayoyi na mu'ujiza su zo musu. To sai Allah ya mayar musu da martanin cewa, ai ranar da Ubangiji zai zo musu ita ce alƙiyama don yi musu hisabi ko kuma idan rana ta hudo musu ta mafaɗarta. To duk lokacin da rana za ta fito daga mafaɗarta, to a wannan rana babu wani rai da bai yi imani ba wanda imaninsa zai amfane shi; a ranar ba za a karɓi tuban mai tuba ba ko wani aiki na ƙwarai ga wanda bai yi wani aiki na ƙwarai gabanin haka ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, su saurari zuwan ɗaya daga cikin waɗannan abubuwan, shi ma tare da muminani masu sauraro ne.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Manzon Allah (ﷺ) ya tambayi sahabbai cewa: "Kun san ina rana take tafiya?" Sai suka ce: "Allah da Manzonsa ne mafi sani." Sai ya ce: "Lalle rana tana gudu har sai ta kai ƙarƙashin Al-Arshi, sai ta faɗi ta yi sujjada, ba za ta gushe ba cikin sujjada har sai an ce mata: "Ki ɗago, ki koma inda kika fito." Sai gari ya waye ta fito ta mahudarta, sannan ta yi ta gudu har sai ta kai ƙarshen zangonta, wato ƙarƙashin Al-Arshi, sai ta faɗi ta yi sujjada, ba za ta gushe ba cikin sujjada har sai an ce mata: "Ɗago ki koma inda kika fito." Sai a wayi gari ta fito daga mahudarta, mutane ba su ga wani canji tare da ita ba, sai ta yi ta gudu har sai ta kai ƙarshen zangonta, wato ƙarƙashin Al-Arshi, sai a ce mata: "Ɗago gobe da safe ki fito ta mafaɗarki." Sai a wayi gari rana ta fito ta mafaɗarta." Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ko kun san yaushe haka zai faru? Haka zai faru ne lokacin da imanin wani rai ba zai amfane shi ba, idan a da can bai yi imani ba ko bai aikata wani abu na alheri a cikin imaninsa ba." [Muslim #159].

Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda suka bar addinin Allah ko suka rarrabu ƙungiya-ƙungiya, to ba ruwan Manzon Allah da su da abin da suke aikatawa; al'amarinsu da makomarsu suna ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sannan a ranar alƙiyama zai ba su labarin duk abin da suka aikata, ya kuma yi musu sakamako a kan ayyukansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ninninka sakamakon kyakkyawan aiki, wannan yana daga cikin falalarsa da ni'imarsa ga bayinsa.

2. Musulunci addini ne na Tauhidi; Allah yana umartar bayinsa da su tsantsanta duk ayyukansu gare shi shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba.

3. Rayuwar bawa gaba ɗayanta dole ne ya gudanar da ita a kan tsarin Allah, ba yadda ya ga dama ba. Babu wani abu na rayuwar ɗan'adam da babu Allah a ciki. Wannan yana rusa akidar masu cewa, babu addini a siyasa, wato sha'anin gudanar da mulkin ƙasa da al'umma.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) har koyaushe yana tunatar da bawa ni’imomin da ya yi masa marasa iyaka, domin ya riƙa yi masa godiya ta hanyar kiyaye dokokinsa.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai halicci mutane a kan matsayi ɗaya ba; ya fifita wasu a kan wasu domin rayuwarsu ta gudana bisa taimakon juna da buƙatar juna. Wannan kuwa yana nuna cikakkiyar hikimar Allah a cikin ayyukansa.

6. Dole ne ga Musulmi ya haɗa tsoro da fata a bautar Allah, watau yana tsoron azabarsa, yana kuma fatan samun rahamarsa. Waɗannan su ne fukafukan bawa guda biyu da ba zai iya tashi ba sai da su, rashin ɗaya daga cikinsu yana nufin halakarsa.

Suratul An’am (160-165)

مَن جَآءَ بِٱلۡحَسَنَةِ فَلَهُۥ عَشۡرُ أَمۡثَالِهَاۖ وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَلَا يُجۡزَىٰٓ إِلَّا مِثۡلَهَا وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ١٦٠ قُلۡ إِنَّنِي هَدَىٰنِي رَبِّيٓ إِلَىٰ صِرَٰطٖ
مُّسۡتَقِيمٖ دِينٗا قِيَمٗا مِّلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۚ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١٦١ قُلۡ إِنَّ صَلَاتِي وَنُسُكِي وَمَحۡيَايَ وَمَمَاتِي لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٦٢ لَا شَرِيكَ
لَهُۥۖ وَبِذَٰلِكَ أُمِرۡتُ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ١٦٣ قُلۡ أَغَيۡرَ ٱللَّهِ أَبۡغِي رَبّٗا وَهُوَ رَبُّ كُلِّ شَيۡءٖۚ وَلَا تَكۡسِبُ كُلُّ نَفۡسٍ إِلَّا عَلَيۡهَاۚ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ
أُخۡرَىٰۚ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُم مَّرۡجِعُكُمۡ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ ١٦٤ وَهُوَ ٱلَّذِي جَعَلَكُمۡ خَلَٰٓئِفَ ٱلۡأَرۡضِ وَرَفَعَ بَعۡضَكُمۡ فَوۡقَ بَعۡضٖ
دَرَجَٰتٖ لِّيَبۡلُوَكُمۡ فِي مَآ ءَاتَىٰكُمۡۗ إِنَّ رَبَّكَ سَرِيعُ ٱلۡعِقَابِ وَإِنَّهُۥ لَغَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٦٥

160. Wanda ya zo da kyakkyawan aiki ɗaya, to yana da ninkin ladansa goma; wanda kuwa ya zo da mummuna ɗaya, to ba za a saka masa ba sai daidai da shi, ba kuma za a zalunce su ba.

161. Ka ce: “Lalle ni, Ubangijina Ya shiryar da ni zuwa ga tafarki madaidaici, shi ne addini miƙaƙƙe, addinin Ibrahimu wanda ya karkace wa ɓarna, kuma bai zama daga masu shirka ba.”

162. Ka ce: “Lalle sallata da yankana da rayuwata da mutuwata, duk na Allah ne Ubangijin talikai.

163. “Ba Shi da abokin tarayya; kuma da hakan aka umarce ni, kuma ni ne farkon Musulmai.”

164. Ka ce: “ Yanzu wanin Allah zan riƙa a matsayin ubangiji, alhalin kuwa Shi ne Ubangijin komai? Kuma ba wani rai da zai aikata wani abu face sai don kansa. Kuma ba wani rai da zai ɗauki laifin wani rai. Sannan kuma zuwa ga Ubangijinku ne makomarku take, sai Ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna saɓani a game da shi.

165. “Kuma Shi ne Ya sanya ku halifofi a bayan ƙasa, kuma Ya ɗaukaka darajar wasunku a kan wasu, don Ya jarrabe ku game da abin da Ya ba ku. Lalle Ubangijinka Mai gaggawar uƙuba ne, kuma lalle Shi tabbas Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin ƙai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa, duk wanda ya yi wani kyakkyawan aiki, to ranar alƙiyama yana da riɓinsa goma, wanda kuwa ya yi mummuna, to ba za a saka masa ba sai da kwatankwacin abin da ya aikata, kuma babu wanda Allah zai zalunce shi da komai.
An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ruwaito daga Ubangijinsa yana cewa: “Lalle Allah ya rubuta kyawawan ayyuka da munana sannan ya yi bayaninsu: Wanda ya ƙuduri aniyar aikata wani kyakkyawan aiki sai bai aikata ba, to za a rubuta masa cikakken lada a wurin Allah; idan kuwa ya yi niyyar aikatawa kuma ya aikata, to za a rubuta masa ladan kyawawan

ayyuka goma har zuwa ninki ɗari bakwai, zuwa ninki ba iyaka; wanda kuwa ya yi niyyar aikata mummunan aiki sai bai aikata ba, to za a rubuta masa cikakken ladan kyakkyawan aiki; idan kuwa ya yi niyyar aikata mummunan aiki sai ya aikata, to Allah zai rubuta masa zunubin mummunan aiki ɗaya." [Bukhari #6491, da Muslim #130].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya bayyana cewa, shi kam Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiryar da shi zuwa ga miƙaƙƙiyar hanya, addinin da yake tsaye da adalci wanda shi ne shari'ar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya tsaya ƙyam a kan gaskiya, ya bar duk wata ɓarna da hanyoyin ɓata, kuma bai taɓa zamowa a cikin masu shirka ba.

Ya kuma umarce shi ya bayyana musu cewa, sallarsa da yankansa da rayuwarsa da mutuwarsa duk a hannun Allah suke shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, ya jaddada musu cewa, shi ma da wannan ne aka umarce shi, kuma shi ne farkon masu miƙa wuya.Sannan ya umarce shi ya tambayi mushirikai cewa, shin yanzu su a ganinsu ya dace a ce ya riƙi wani ubangiji daban ban da Allah, wanda kuma shi ne Ubangijin kowa da komai? Kuma ya san cewa duk laifin da mutum zai aikata, alhakinsa yana kansa babu mai ɗauke masa, kuma babu wani rai da yake ɗauke wa wani rai komai na laifukansa, kowa shi ne mai ɗaukar nauyin zunubin aikinsa, kuma makomar kowa zuwa ga Allah ne, zai kuma yi musu bayanin abin da suka riƙa aikatawa a duniya, kuma zai warware musu abin da suke yin saɓani a kansa.

Kuma shi ne wanda ya mayar da su halifofi a bayan ƙasa bayan ya halaka al'ummomin farko, ya kuma ɗaukaka darajar wasu a kan wasu, don ya jarraba su a kan abin da ya ba su na falalarsa da ni'imarsa, domin ya ga kamun ludayin kowa. Lalle Allah mai gaggauta azaba ne, kuma mai yawan gafara ne mai jin ƙai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ga Musulmi ya riƙa tuntuntuni game da Alƙur'ani, yana fahimtar umarninsa da haninsa da abin da ya halatta da abin da ya haramta ya yi aiki da su, ya tabbatar da abin da yake cikinsa na ingantacciyar aƙida.

2. Kada wani Musulmi ya riƙe wasu ba Allah ba yana bin su sau-da-ƙafa kamar yadda ake bin Allah da Manzonsa (ﷺ). Wanda duk ya yi haka, to ya nesanta kansa daga Allah da Manzonsa (ﷺ).

3. Alƙur'ani ya zo ne don ya kawar da duk wani ƙunci ko damuwa ta zukata, don haka duk wanda ya riƙe shi, to zai samu cikakkiyar waraka daga duk wani ƙuncin zuciya da damuwa.

7-Suratul A’araf

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna *‘Suratul A’araf’*. An ba ta wannan suna ne kuwa saboda an ambaci wannan lafazin a cikinta. Watau an yi bayanin mutanen tozon La’arfi a lahira, babu kuma inda aka yi bayaninsu sai a wannan Surar.
An karɓo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ƙaranta *Suratul A’raf* a sallar Magriba, ya kuma raba ta biyu a cikin raka’o’insa biyu.

An karɓo daga Zaidu ɗan Sabitu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce wa Marwan ɗan Hakam: “Mene ne ya sa nake ganin ka a sallar Magriba kana ƙaranta gajejjerun surori, alhalin haƙiƙa ni na ga Manzon Allah a sallar Magriba yana ƙaranta ɗaya daga cikin dogayen surorin nan biyu?” Sai Marwan ya tambaye shi: “Wacce Sura ce wannan mai tsawo?” Sai ya ce masa: *“Al-a’raf*”.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Wannan Sura *Makiyya* ce, kamar yadda wasu malamai suka ambato ijma’i a kan hakan.

3. Jerin Saukarta:
Ana lissafa ta a Sura ta talatin da tara (39) a jerin saukar surori. Ta sauka bayan *‘Suratu Sad’*, gabanin *‘Suratul Jinn’*.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Madina da Kufa adadin ayoyinta ɗari biyu ne da shida (206). Amma a lissafin mutanen Sham da Basra, ayoyinta ɗari biyu da biyar ne (205).

5. Babban Jigonta:
• Lallashin Annabi (ﷺ) game da ƙaryata shi da kafirai suke yi.
• Bayanin jigogin aƙida da manya-manyan ƙa’idoji na addini.
• Bayanin dogon zangon da ‘yan’adam suka keto tun farkon halittar Annabi Adamu har zuwa tashin alƙiyama.

6. Daga Cikin Abubuwa Da Ta ƙunsa Akwai:
• Ishara zuwa ga girman darajar Alƙur’ani mai girma.
• Hana bautar wasu tare da Allah da gargaɗin mushirikai a kan mummunar makomar shirka a duniya da lahira da bayanin azabar da ta auka wa mushiriai da masu ƙaryata manzanni a nan duniya da abin da zai same su a lahira da kafa dalilai masu nuna Ɗayantakar Allah.

• Magana a kan auna ayyukan mutane a lahira da tuna musu ni’imomin da Allah ya yi musu a bayan ƙasa ya hore wa ɗan’adam amfani da su.
• Bayanin halittar Annabi Adamu da abin da ya biyo bayanta na sujjadar mala’iku a gare shi domin biyayya ga Allah da bijirewar Shaiɗan da yadda ya bayyana tsananin hassadarsa da gabarsa ga Annabi Adamu da zurriyarsa da alwashin da ya ɗauka a gaban Allah na cewa sai ya hallaka su in ban da zaɓaɓɓun bayinsa. Da bayanin yadda ya fara da saka waswasi ga Adamu da matarsa Hauwa’u har suka ci itaciyar da Allah ya hana su ci, aka saukar da su a doron ƙasa baki ɗaya.
• Magana a kan ƙissar mutanen tozon La’arafi da tunatarwa a game da tashin alƙiyama.
• Hani a kan yaɗa ɓarna a bayan ƙasa bayan Allah ya gyara ta don amfanin ɗan’adam.
• Ambaton labaran manzannin Allah tare da mutanensu tun daga Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) har zuwa Musa da Fir’auna da mutanensa.
• Tsoratarwa game da amincewa da makircin Allah, yayin da jinkirta wa masu laifi zai sa su su ruɗu su zarme cikin saɓon Allah.
• Bushara da aiko Annabi (ﷺ) da ambaton wasu daga cikin siffofinsa a littattafan Attaura da Linjila.
• Umartar Musulmi da ɗabi’antuwa da wasu halaye masu kyau, kamar yin afuwa da yafiya da kuma ci gaba da ƙoƙari wajen kira zuwa ga Allah da haƙuri a kan haka.
• Da sauran mahimman batutuwa da Surar ta ƙunsa.

Suratul A’araf (1-3)

الٓمٓصٓ ۝١ كِتَٰبٌ أُنزِلَ إِلَيۡكَ فَلَا يَكُن فِي صَدۡرِكَ حَرَجٞ مِّنۡهُ لِتُنذِرَ بِهِۦ وَذِكۡرَىٰ لِلۡمُؤۡمِنِينَ ۝٢ ٱتَّبِعُواْ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكُم مِّن رَّبِّكُمۡ وَلَا تَتَّبِعُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَۗ قَلِيلٗا مَّا تَذَكَّرُونَ ۝٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. *Alif Laam Miim Saad*.

2. (Wannan) Littafi ne da aka saukar maka, don haka kada wani ƙunci ya kasance a ƙirjinka a sanadiyyarsa, don ka yi gargaɗi da shi, kuma da tunatarwa ga muminai.

3. Ku bi abin da aka saukar muku daga Ubangijinku, kada kuma ku bi wasu masoya ba shi ba. Kaɗan ne ƙwarai kuke wa’azantuwa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar mai girma da haruffa irin waɗanda ya buɗe surorin *Al-Baƙara* da *Ali Imrana* su. Malaman tafsiri sun yi batutuwa masu yawa a kan bayanin manufofin waɗannan haruffa. Magana mafi rinjaye ita ce mai cewa, waɗannan harrufa an kawo su ne don bayyana mu’ujizar Alƙur’ani, wato shi littafi ne da ya ƙunshi haruffan da Larabawa suke magana da rubutu da su. To idan suna ganin Alƙur’ani ba daga Allah yake ba, to su kawo wata magana kwatankwacinsa idan za su iya. Shi ya sa a duk inda aka buɗe wata Sura da waɗannan haruffa, to magana a kan Alƙur’ani ne takan biyo bayansu, domin alaƙar da ke tsakaninsu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, Alƙur’ani littafi ne da ya saukar masa, don haka kada ya samu wani ƙunci a ƙirjinsa game da isar da saƙon da yake cikinsa, kuma ya yi gargaɗi da wa’azi da shi, kada ya yi shakkar kasancewarsa saukakke ne daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Allah ya saukar da shi ne domin ya tsoratar da kafirai da shi, ya kuma zama wa’azi ga muminai.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mutane da su bi abin da ya zo a wannan Alƙur'ani, kuma su yi aiki da shi, kada su bi wasu majiɓinta ba shi ba, sai su raba su da koyarwar Alƙur'ani da sunnar Manzo (ﷺ). Allah ya ba da labarin cewa, kaɗan ne masu wa'azantuwa su ɗauki darasi su koma ga gaskiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samun walwala ta yau da kullum da samun arziki na duniya kada su saka bawa ya miƙe ƙafa, ya zaci cewa Allah ya yi masa haka ne don ya cancanta; koyaushe ya riƙa tuna Allah da girmansa, ya yi taka-tsantsan game da saɓa masa.

2. Kowa sai an yi masa tambayoyi a ranar alƙiyama.

3. Tambayar da za a yi wa manzanni, za a yi ta ne da nufin tabbatar da sun isar da saƙo, ba su yi ƙasa-a-gwiwa ba, don haka wannan zai ƙara musu daraja ne da matsayi a ranar alƙiyama.

4. Cikar adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da rahamarsa. Zai auna ayyukan bawa, ya yi masa sakamako a kan abin da ya yi rinjaye, mai kyau ko marar kyau.

Suratul A'araf (4-9)

وَكَم مِّن قَرۡيَةٍ أَهۡلَكۡنَٰهَا فَجَآءَهَا بَأۡسُنَا بَيَٰتًا أَوۡ هُمۡ قَآئِلُونَ ۝٤ فَمَا كَانَ دَعۡوَىٰهُمۡ إِذۡ جَآءَهُم بَأۡسُنَآ إِلَّآ أَن قَالُوٓاْ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ۝٥ فَلَنَسۡـَٔلَنَّ ٱلَّذِينَ أُرۡسِلَ إِلَيۡهِمۡ وَلَنَسۡـَٔلَنَّ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ۝٦ فَلَنَقُصَّنَّ عَلَيۡهِم بِعِلۡمٖۖ وَمَا كُنَّا غَآئِبِينَ ۝٧ وَٱلۡوَزۡنُ يَوۡمَئِذٍ ٱلۡحَقُّۚ فَمَن ثَقُلَتۡ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ۝٨ وَمَنۡ خَفَّتۡ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُم بِمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَظۡلِمُونَ ۝٩

4. Kuma nawa-nawa ne daga cikin alƙaryu waɗanda Muka (nufi) halaka su, sai azabar mu ta zo musu da daddare ko lokacin da suke barcin ƙailula?

5. Sannan ba abin da suke faɗa, lokacin da azabarmu ta zo musu sai cewa: "Lalle mu mun kasance azzalumai."

6. To lalle tabbas sai Mun tambayi waɗanda aka aiko musu manzanni, kuma lalle tabbas, sai mun tambayi manzannin (su kansu).

7. Kuma lalle za Mu ba su labarin (komai) da ilimi; kuma ba Mu zamanto ba ma nan ba.

8. Awo kuma a wannan ranar gaskiya ne. Don haka duk wanda ma'aunansa suka yi nauyi, to waɗannan su ne masu rabauta.

9. Wanda kuwa ma'aunansa suka yi sakayau, to waɗannan su ne waɗanda suka yi hasarar kawunansu, saboda abin da suka kasance suna yi na zalunci da ayoyinmu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa, a baya can ya halaka garuruwa masu yawa waɗanda mutanen cikinsu suka riƙa bautar wasu ba Allah ba, suka kuma ƙaryata

manzannin da ya aiko musu. Azabar Allah kuma ta sauko musu ne ba zato ba tsammani, ta zo musu ne suna barci cikin dare, wasu kuma suna tsakiyar barci da rana, wato ƙailula. Yayin da azabar ta sauko musu, babu abin da suka riƙa faɗa sai iƙirarin cewa su kam lalle azzalumai ne.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana, cewa zai tsare duk wata al'umma ranar Alƙiyama ya tambaye su game da abin da manzanninsu suka je musu da shi, kuma shin sun yi musu biyayya ko ba su yi ba? Sun gaskata su ko kuma ƙaryata su suka yi? Hakanan su ma manzannin sai Allah ya tambaye su, shin sun isar da manzancin da ya ba su ko kuma a'a? Al'ummominsu sun yarda da su ko sun ƙaryata su?An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle kowannenku mai kiwo ne, kuma sai an tambayi kowa game da abin kiwonsa, mai mulkin mutane mai kiwo ne, kuma za a tambaye shi game da abin kiwonsa, magidanci mai kiwo ne ga iyalansa, kuma sai an tambaye shi game da su, mace mai kiwo ce a gidan mijinta da 'ya'yansa, kuma sai an tambaye ta game da su, bawa mai kiwo ne a kan dukiyar maigidansa, kuma sai an tambaye shi a kan wannan. Don haka ku duka masu kiwo ne, kuma za a tambaye ku a kan abin kiwonku." [Bukhari #893 da Muslim #1829].

An karɓo daga Abu Barzatul Aslami (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ranar alƙiyama digadigan bawa ba za su gushe ba har sai an yi masa tambaya game da rayuwarsa, a me ya ƙarar da ita, iliminsa me ya aikata da shi, da dukiyarsa a ina ya same ta, kuma yaya ya kashe ta, da ganganr jikinsa yaya ya yi amfani da ita." [Tirmizi #2417 da Darimi #537].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, zai ba wa bayinsa labari na ilimin ranar alƙiyama game da abin da suka faɗa ko suka aikata a duniya, kuma shi Allah babu wani lokaci da za a ce ba ya tare da bayinsa yana ganin abin da suke aikatawa.
Hakanan kuma ya bayyana cewa, awon ayyuka a ranar alƙiyama gaskiya ne, Allah zai auna ayyukan bayinsa bisa adalci. Waɗanda ma'aunan kyawawan ayyukansu suka yi nauyi, to waɗannan su ne masu babban rabo; waɗanda kuwa ma'aunan ayyukansu masu kyau suka yi sakayau, wato munanan ayyukansu suka rinjayi kyawawansu, to waɗannan su ne suka tafka asara ga kawunansu sakamakon ƙaryata ayoyin Allah da jayayya da su da suka yi.

An karɓo daga Abud Darda'i (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani abu da zai fi kyawawan halaye nauyi a ma'auni (ranar alƙiyama), da kyawawan halaye mutum zai kai matsayin mai yawan azumi da salla (na nafila)." [Abu Dawud #4799, da Tirmizi #2003, da Ahmad #27557].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rashin godiyar Allah a kan wata ni'imarsa yana jawowa a rasa ta gaba ɗaya.

2. Halittar ɗan'adam daga babu da inganta surarsa, wata babbar ni'ima ce gare shi da ya wajaba ya gode wa mahaliccinsa a kai.

3. Wajibi ne ga bawa ya bi umarnin Ubangijinsa ko da abin da aka umarce shi da shi bai yi masa daɗi ba.

4. Ji-ji da kai yana daga cikin abubuwan da suka halaka Iblis.

5. Alfahari da asali aikin Shaiɗan ne.

6. Yi wa Allah girman kai yana jawo wa bawa azabar Allah mai tsanani da kora daga gungun masoya Allah.

7. Mai girman kai ba zai shiga Aljanna ba, domin babu girman kai a cikinta.

8. Game da jinkirta wa Iblis akwai hikima ta Ubangiji, wato don ya jarrabi bayinsa da shi don ya bayyana mai yi masa biyayya da mai saba masa.

9. Iblis ya fahimci girman matsayin godiyar Allah, shi ya sa ya sha alwashin hana bayi gode wa Allah.

10. Iblis ya san hanyar gaskiya, don haka ya yi rantsuwar cewa sai ya zaune wa bayi wannan hanyar, ya hana su bin ta.

Suratul A'araf (10-18)

وَلَقَدۡ مَكَّنَّٰكُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَجَعَلۡنَا لَكُمۡ فِيهَا مَعَٰيِشَۗ قَلِيلٗا مَّا تَشۡكُرُونَ ١٠ وَلَقَدۡ خَلَقۡنَٰكُمۡ ثُمَّ صَوَّرۡنَٰكُمۡ ثُمَّ قُلۡنَا لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ ٱسۡجُدُواْ لِأٓدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبۡلِيسَ لَمۡ يَكُن مِّنَ ٱلسَّٰجِدِينَ ١١ قَالَ مَا مَنَعَكَ أَلَّا تَسۡجُدَ إِذۡ أَمَرۡتُكَۖ قَالَ أَنَا۠ خَيۡرٞ مِّنۡهُ خَلَقۡتَنِي مِن نَّارٖ وَخَلَقۡتَهُۥ مِن طِينٖ ١٢ قَالَ فَٱهۡبِطۡ مِنۡهَا فَمَا يَكُونُ لَكَ أَن تَتَكَبَّرَ فِيهَا فَٱخۡرُجۡ إِنَّكَ مِنَ ٱلصَّٰغِرِينَ ١٣ قَالَ أَنظِرۡنِيٓ إِلَىٰ يَوۡمِ يُبۡعَثُونَ ١٤ قَالَ إِنَّكَ مِنَ ٱلۡمُنظَرِينَ ١٥ قَالَ فَبِمَآ أَغۡوَيۡتَنِي لَأَقۡعُدَنَّ لَهُمۡ صِرَٰطَكَ ٱلۡمُسۡتَقِيمَ ١٦ ثُمَّ لَأٓتِيَنَّهُم مِّنۢ بَيۡنِ أَيۡدِيهِمۡ وَمِنۡ خَلۡفِهِمۡ وَعَنۡ أَيۡمَٰنِهِمۡ وَعَن شَمَآئِلِهِمۡۖ وَلَا تَجِدُ أَكۡثَرَهُمۡ شَٰكِرِينَ ١٧ قَالَ ٱخۡرُجۡ مِنۡهَا مَذۡءُومٗا مَّدۡحُورٗاۖ لَّمَن تَبِعَكَ مِنۡهُمۡ لَأَمۡلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنكُمۡ أَجۡمَعِينَ ١٨

10. Kuma lalle haƙiƙa Mun kafa ku a bayan ƙasa, kuma Muka sanya muku wuraren rayuwa a cikinta. Kaɗan ne ƙwarai kuke godiya.

11. Kuma lalle haƙiƙa Mun halicce ku, sannan kuma Muka suranta ku; sannan Muka ce wa mala'iku: "Ku yi sujjada ga Adamu," sai suka yi sujjada, sai Iblis ne kaɗai bai kasance cikin masu sujjada ba.

12. (Allah) Ya ce: "Me ya hana ka yin sujada lokacin da Na umarce ka?" Sai ya ce: "Ai ni na fi shi alheri; Ka halicce ni da wuta, shi kuwa Ka halicce shi da taɓo."

13. Sai Ya ce: "To ka sauka daga cikinta, bai dace gare ka ka yi girman kai a cikinta ba, don haka sai ka fita, lalle kai kana cikin ƙasƙantattu."

14. Sai ya ce: "Ka yi min jinkiri zuwa ranar da za a tashe su (mutane)."

15. Sai Ya ce: "Lalle kai kana cikin waɗanda za a yi wa jinkiri."

16. Ya ce: "Saboda ɓatar da ni da Ka yi, lalle sai na zaune musu tafarkinka madaidaici.

17. "Sannan lalle zan zo musu ta gabansu da kuma ta bayansu da kuma ta damansu, da kuma ta hagunsu; kuma ba za Ka samu yawancinsu masu godiya ba."

18. Ya ce: "Ka fita daga cikinta kana abin aibatawa, korarre (daga rahama); Na rantse duk wanda ya bi ka daga cikinsu, lalle zan cika Jahannama da ku gaba ɗaya."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin wasu ni'imomin da ya yi wa bayinsa ne, wato ya samar musu da shimfiɗaɗɗiyar ƙasa, ya ba su damar amfana da ita da sauran buƙatun rayuwarsu, to amma duk da wannan bayinsa masu gode masa 'yan kaɗan ne.
Sannan kuma wata babbar ni'ima da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu wadda ba kowa ne yake tunawa da ita ba har ya gode ita ce, halittar Babansu Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da taɓo, ya suranta shi cikakken mutum, sai ya ce wa mala'iku su yi masa sujjada, sai su duka suka faɗi suka yi masa sujjada kamar yadda Allah ya umarce su, sai Iblisu ne kaɗai ya ƙi yin sujjada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye shi ya faɗi dalilin da ya hana shi yi wa Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sujjada bayan ya umarce shi da hakan. Sai ya amsa da cewa, ai shi wai ya fi Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daraja, domin shi an halicce shi da wuta, shi kuma Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) an halicce shi da taɓo.
To saboda wannan girman kai da Iblisu ya nuna, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya sauko daga gidan Aljanna, domin ba a yarda da girman kai a cikinta ba, ya kuma sani cewa yana cikin ƙaskantattu waɗanda ba za su ƙara martaba ba a wurin Allah.
To bayan korar Iblisu daga gidan Aljanna, sai ya roƙi Allah ya jinkirta masa rayuwarsa har zuwa ranar tashin alƙiyama. Allah kuma ya ce ya je an saurara masa har zuwa wannan lokaci. Daga nan sai Iblis ya yi rantsuwa da Ubangijinsa cewa, saboda ɓatar da shi da Allah ya yi, lalle zai zauna ya yi kane-kane a kan madaidaiciyar hanya da Allah zai ɗora 'yan'adam a kanta, ya hana musu bin ta, ya ƙawata musu hanyar ƙarya da ɓarna. Kuma ya sha alwashin sai ya ɓullo musu ta hanyoyi da dama, ta gabansu da ta bayansu da ta damansu da ta hagunsu, don ya tabbatar ya ɓatar da su daga kan madaidaiciyar hanya. Kuma da yawa ba zai bar mutane su riƙa gode wa Allah ba.

An karɓo daga Sabra ɗan Abu Fakihin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Shaiɗan ya zauna ya yi kane-kane a kan hanyoyin ɗan'adam; ya zaune masa hanyar shiga Musulunci, ya ce masa: 'Yanzu ka musulunta ka bar addininka kuma addinin iyayenka?' Sai ya ƙi yarda, ya musulunta. Sai kuma ya zaune masa hanyar yin hijira, ya ce masa: 'Yanzu ka yi hijira ka fita daga ƙasarka da samaniyarka. Misalin ɗan hijira kamar misalin doki ne a ɗaure a doguwar igiya.' Sai ya ƙi yarda da shi, ya fita ya yi hijira. Sannan sai ya zaune masa hanyar fita jihadi, ya ce masa: 'Shi jihadi wahalar da kai ne da kashe dukiya, yanzu ka fita yaƙi a kashe ka a aure matarka, a raba dukiyarka.' Sai ɗan'adam ya saɓa masa, ya fita jihadi." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya aikata haka daga cikin mutane har ya mutu, to haƙƙi ne a kan Allah ya shigar da shi gidan Aljanna, ko aka kashe shi, haƙƙi ne a kan Allah ya shigar da shi Aljanna, ko ya nutse a cikin ruwa ya mutu, haƙƙi ne a kan Allah ya shigar da shi Aljanna, ko dabba ta harbe shi ya mutu, haƙƙi ne a kan Allah ya shigar da shi Aljanna." [Nasa'i #3134, da Ahmad #16000, da Ibn Hibban #4593].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Iblis da ya fita daga gidan Aljanna yana abin zargi, korarre daga rahamar Allah. Ya kuma rantse cewa, duk wanda ya bi Iblis sai ya cika gidan wutar Jahannama da su gaba ɗaya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne a kan Musulmi ya guje wa wuraren tuhuma, watau kada ya kusanci duk wurin da ake saɓon Allah, don gudun kada Shaiɗan ya ingiza shi bai an ƙara ba.

2. Shaiɗan yakan iya yaudarar annabawa da niyyar ya ɓatar da su, amma wannan ba ya zama abin suka ga annabcinsu.

3. Saɓon Allah yana keta suturar da Allah yake yi wa bawansa har tsiraicinsa na zahiri da na baɗini su bayyana ga masu kallo. Don haka babu abin da zai yi wa bawa sutura da kariya kamar tsoron Allah.

4. Duk irin matsayin da bawa zai kai, to saɓon Allah yana iya sauko da shi daga wannan matsayin cikin ƙanƙanin lokaci.

5. Yana da kyau bawa ya zama mai ladabi yayin da yake addu'a yana roƙon Allah. Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Hawwa'u ba su jingina wa ƙaddarar Allah laifinsu ba; sun jingina shi ne ga kawunansu kai-tsaye. Wannan yana daga cikin ladubban roƙon Allah.

6. Suturce al'aura wajibi ne.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana magana sa'adda ya ga dama, ga wanda ya ga dama, a lokacin da ya ga dama.

8. Wanda ya yi laifi ya tuba, to ya kwaikwayi babansa Annabi Adamu ne; wanda kuwa ya kafe a kan laifinsa, ya kafa hujja da ƙaddara, to yana kwaikwayon Iblis ne.

Suratul A'araf (19-25)

وَيَٰٓـَٔادَمُ ٱسۡكُنۡ أَنتَ وَزَوۡجُكَ ٱلۡجَنَّةَ فَكُلَا مِنۡ حَيۡثُ شِئۡتُمَا وَلَا تَقۡرَبَا هَٰذِهِ ٱلشَّجَرَةَ فَتَكُونَا مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ١٩ فَوَسۡوَسَ لَهُمَا ٱلشَّيۡطَٰنُ لِيُبۡدِيَ لَهُمَا مَا وُۥرِيَ عَنۡهُمَا مِن سَوۡءَٰتِهِمَا وَقَالَ مَا نَهَىٰكُمَا رَبُّكُمَا عَنۡ هَٰذِهِ ٱلشَّجَرَةِ إِلَّآ أَن تَكُونَا مَلَكَيۡنِ أَوۡ تَكُونَا مِنَ ٱلۡخَٰلِدِينَ٢٠ وَقَاسَمَهُمَآ إِنِّي لَكُمَا لَمِنَ ٱلنَّٰصِحِينَ٢١ فَدَلَّىٰهُمَا بِغُرُورٖۚ فَلَمَّا ذَاقَا ٱلشَّجَرَةَ بَدَتۡ لَهُمَا سَوۡءَٰتُهُمَا وَطَفِقَا يَخۡصِفَانِ عَلَيۡهِمَا مِن وَرَقِ ٱلۡجَنَّةِۖ وَنَادَىٰهُمَا رَبُّهُمَآ أَلَمۡ أَنۡهَكُمَا عَن تِلۡكُمَا ٱلشَّجَرَةِ وَأَقُل لَّكُمَآ إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ لَكُمَا عَدُوّٞ مُّبِينٞ٢٢ قَالَا رَبَّنَا ظَلَمۡنَآ أَنفُسَنَا وَإِن لَّمۡ تَغۡفِرۡ لَنَا وَتَرۡحَمۡنَا لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ٢٣ قَالَ ٱهۡبِطُواْ بَعۡضُكُمۡ لِبَعۡضٍ عَدُوّٞۖ وَلَكُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُسۡتَقَرّٞ وَمَتَٰعٌ إِلَىٰ حِينٖ٢٤ قَالَ فِيهَا تَحۡيَوۡنَ وَفِيهَا تَمُوتُونَ وَمِنۡهَا تُخۡرَجُونَ٢٥

19. "Kuma ya kai Adam, ka zauna cikin Aljanna, da kai da matarka, kuma ku ci duk abin da kuka ga dama, amma kada ku kusanci wannan bishiyar, sai ku kasance cikin azzalumai."

20. Sai Shaiɗan ya yi musu waswasi, domin ya bayyana musu abin da aka ɓoye musu na tsiraicinsu, kuma ya ce: "Ba abin da ya sa Ubangijinku Ya hane ku daga wannan bishiyar, sai don kawai kada ku zama mala'iku ko kuma ku zama daga cikin dawwamammu."

21. Kuma ya yi musu rantsuwa cewa: "Lalle ni mai yi muku nasiha ne."

22. Sai ya yaudare su da ruɗi. Don haka yayin da suka ɗanɗani wannan bishiyar, sai tsiraicinsu ya bayyana a gare su, sai suka fara lulluɓa da ganyayen Aljanna; sai Ubangijinsu Ya kira su: "Yanzu ban hana ku cin wannan bishiyar ba, ban kuma ce da ku ba lalle Shaiɗan maƙiyi ne a gare ku mabayyani?"

23. Sai suka ce: "Ya Ubangijinmu, lalle kam mun zalunci kawunanmu, kuma idan har ba Ka yi mana gafara ba, kuma ba Ka ji ƙan mu ba, to lalle fa za mu kasance cikin hasararru."

24. Sai Ya ce: “Ku sauka, sashinku zai zama abokin adawa ga sashi; kuma kuna da wurin zama a ƙasa da abin jin daɗi zuwa ɗan wani lokaci.”

25. Ya ce: “A cikinta za ku rayu, kuma a cikinta za ku mutu, kuma daga cikinta za a fito da ku.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da matarsa Hawwa’u da su zauna a gidan Aljanna, kuma su ci abin da suke so na ‘ya’yan itatuwanta, amma kada su kusanci wata bishiya da ya nuna musu, don yin hakan zai sanya su cikin azzalumai, wato waɗanda suka cuci kawunansu da rashin biyayya ga Allah da saɓa umarninsa.
Sai Shaiɗan ya sa wa Annabi Adamu da matarsa Hawwa’u waswasi, domin ya yaudare su ya raba su da suturar da ta rufe musu tsiraicinsu. Ya yi musu ƙaryar cewa, Allah bai hana su cin wannan bishiya ba sai don kada su zama mala’iku ko kuma su dawwama a gidan Aljanna. Ya yi musu rantsuwa har da Allah cewa, wannan magana da yake faɗa musu nasiha ce yake yi musu. Har daga ƙarshe dai ya yaudare su, ya zuga su suka ci ‘ya’yan wannan bishiyar. To lokacin da suka ci sai tsiraicinsu ya bayyana gare su. To ganin haka sai suka riƙa lulluɓe jikinsu da ganyen bishiyoyin gidan Aljanna. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kiran su yana zargin su cewa, ashe ba ya hana su cin wannan bishiyar ba, kuma ya faɗa musu cewa Shaiɗan babban maƙiyinsu ne na sarari? Sai nan da nan suka amsa laifinsu, suka yarda cewa sun zalunci kawunansu; idan kuma ba Allah ya gafarta musu ya ji ƙan su ba, to lalle za su zama daga cikin waɗanda suka taɓe.
Sai daga nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Hawwa’u har da Iblisu cewa, lalle su bar gidan Aljanna su sauko bayan ƙasa, junansu suna masu gaba da juna. A nan ƙasa suna da wurin da za su zauna su rayu, su ji daɗi har zuwa lokacin mutuwarsu, kuma a binne su a cikin ƙasar a kuma tashe su daga ƙaburburansu ranar alƙiyama don yi musu sakayya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya hore wa ɗan’adam tufafin da yake rufe tsiraicinsa da su da waɗanda yake ado da su. Sannan ya nuna masa abin da zai gyara baɗininsa da shi, wato ya kiyaye dokokin da ya saukar masa. Duk da muhimmancin sutura ta zahiri ga ɗan’adam, to amma sutura ta baɗini ta fi muhimmanci gare shi, domin za ta yi masa sutura ne duniya da lahira saɓanin suturar zahiri.

2. Mai jin tsoron Allah da kiyaye dokokinsa ba zai taɓa yarda da tsiraici ba, saboda ya saɓa wa sutura ta baɗini.

3. Ɗan’adam ba ya iya ganin Shaiɗan a cikin halittarsa ta asali, amma shi Shaiɗan da zurriyarsa suna ganin ɗan’adam, shi ya sa suke iya samun damar su fitine shi. Don haka ya zama wajibi ga ɗan’adam ya zama a cikin shiri ko da yaushe.

4. Rashin imani shi ne yake jawo ƙulluwar soyayya tsakanin mutum da shaiɗanu.

5. Umarni da tsayar da adalci da daidaito a cikin komai.

6. Tsayar da salla a cikin kyakkyawar shiga da kula da haƙƙoƙinta kamar yadda suke a shari’a.

7. Wanda ya shiriya ya shiriya ne da taimakon Allah, wanda ya ɓata kuwa, to da man ya cancanci ɓatan ne.

يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ قَدۡ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكُمۡ لِبَاسٗا يُوَٰرِي سَوۡءَٰتِكُمۡ وَرِيشٗاۖ وَلِبَاسُ ٱلتَّقۡوَىٰ ذَٰلِكَ خَيۡرٞۚ ذَٰلِكَ مِنۡ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ لَعَلَّهُمۡ يَذَّكَّرُونَ ٢٦ يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ لَا يَفۡتِنَنَّكُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ كَمَآ أَخۡرَجَ أَبَوَيۡكُم مِّنَ ٱلۡجَنَّةِ يَنزِعُ عَنۡهُمَا لِبَاسَهُمَا لِيُرِيَهُمَا سَوۡءَٰتِهِمَآۚ إِنَّهُۥ يَرَىٰكُمۡ هُوَ وَقَبِيلُهُۥ مِنۡ حَيۡثُ لَا تَرَوۡنَهُمۡۗ إِنَّا جَعَلۡنَا ٱلشَّيَٰطِينَ أَوۡلِيَآءَ لِلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ ٢٧ وَإِذَا فَعَلُواْ فَٰحِشَةٗ قَالُواْ وَجَدۡنَا عَلَيۡهَآ ءَابَآءَنَا وَٱللَّهُ أَمَرَنَا بِهَاۗ قُلۡ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَأۡمُرُ بِٱلۡفَحۡشَآءِۖ أَتَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٢٨ قُلۡ أَمَرَ رَبِّي بِٱلۡقِسۡطِۖ وَأَقِيمُواْ وُجُوهَكُمۡ عِندَ كُلِّ مَسۡجِدٖ وَٱدۡعُوهُ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَۚ كَمَا بَدَأَكُمۡ تَعُودُونَ ٢٩ فَرِيقٗا هَدَىٰ وَفَرِيقًا حَقَّ عَلَيۡهِمُ ٱلضَّلَٰلَةُۚ إِنَّهُمُ ٱتَّخَذُواْ ٱلشَّيَٰطِينَ أَوۡلِيَآءَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَيَحۡسَبُونَ أَنَّهُم مُّهۡتَدُونَ ٣٠

26. Ya ku ‘yan’adam, haƙiƙa Mun saukar muku da tufafi wanda zai suturce muku tsiraicinku, da kayan ado; tufafi na taƙawa kuwa wannan shi ya fi alheri. Wannan yana daga cikin ayoyin Allah, ko sa yi tuntuntuni.

27. Ya ku ‘yan’adam, kada Shaiɗan ya fitine ku kamar yadda ya fitar da iyayenku daga cikin Aljanna, yana mai cire musu tufafinsu don ya nuna musu tsiraicin junansu. Lalle shi yana ganin ku, shi da jama’arsa ta inda ku ba kwa ganin su. Lalle mu Mun sanya shaiɗanu su zamo masoya ga waɗanda ba sa yin imani.

28. Idan kuma sun aikata wani mummunan aiki sai su ce: “Mun sami iyayenmu ne a kansa, kuma Allah ne Ya umarce mu da shi.” Ka ce: “Lalle Allah ba Ya umarni da mummunan aiki; yanzu kwa riƙa faɗin abin da ba ku sani ba kuna jingina wa Allah?”

29. Ka ce: “Ubangijina Ya yi umarni da adalci; kuma ku tsai da fuskokinku (don Allah) a kowace salla, ku kuma roƙe Shi kuna masu tsantsanta addini gare Shi. Kamar yadda Ya fari halittarku, haka za ku koma (wurinsa).

30. Wani sashi Ya shirye su, wani sashin kuma ɓata ya tabbata a kansu. Lalle su sun mayar da shaiɗanu masoya ba Allah ba, suna kuma tsammanin cewa lalle su shiryayyu ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa ‘yan’adam cewa, ya halitta musu tufafin sawa waɗanda suke rufe musu tsiraici da kuma kayan ado, amma su sani cewa tufa ta tsoron Allah ita ta fi alheri. Allah ya nuna cewa, wannan ni’ima da ya yi musu ɗaya ce daga cikin ayoyinsa, ko sa riƙa wa’azantuwa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da su hatsarin Shaiɗan cewa, su yi hattara kada ya ruɗe su kamar yadda ya ruɗi iyayensu Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Hawwa’u, ya ƙawata musu saɓon Allah, har ya fito da su daga gidan Aljanna, yana yaye musu tufafinsu domin ya nuna musu tsiraicinsu. Allah kuma ya faɗa musu cewa, Shaiɗan da zurriyarsa suna ganin su ta inda su ‘yan’adam ba sa ganin su, kuma ya sanya shaiɗanu masoya ga waɗanda ba sa yin imani.
Kafirai kuma idan sun aikata wani mummunan aiki, kamar yin ɗawafi tsirara, sai su riƙa kare kansu da cewa, ai su ma haka suka ga iyayensu suna yi, kuma ma wai Allah ne ya umarce su da yin hakan. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya mayar musu da martani cewa, ai Allah ba ya umarni da mummunan aiki. Yaya za su riƙa ƙagar ƙarya suna jingina wa Allah? Kuma ya umarce shi ya faɗa musu cewa, Ubangijinsa (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni ne da yin adalci, kuma su fuskanci Allah da sallarsu a kowane masallaci, kuma a ko’ina suke, su kuma roƙi Allah suna masu tsantsanta addini gare

shi. Sannan ya tunatar da su farkonsu da ƙarshensu cewa, kamar yadda a karon farko ya halicce su bayan babu su, to hakanan za su koma gare shi ranar alƙiyama. Allah ya shiryar da wani ɓangare daga cikinsu, wasu kuma ɓata ya tabbata a kansu, sun mayar da shaiɗanu masoyansu ba Allah ba, kuma suna tsammanin cewa su shiryayyu ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni ga wanda zai yi salla ya yi kyakkyawar shiga. Sunna ce kuma a kyautata suturar salla, musamman ranar Juma'a da ranar Idi.

2. Haramcin yin almubazzaranci da abinci da abin sha da duk wani abu na dukiya.

3. Babu wanda ya mallaki haƙƙin haramta abin da Allah bai haramta shi ba sai shi kaɗai.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yalwata wa bayinsa abubuwan jin daɗi na rayuwa don su sami ƙarfin bauta masa. Kafiri kuma mai cin arzikin Allah sannan ya butulce masa, sai Allah ya tambaye shi a ranar gobe ƙiyama game da abin da ya amfana da shi na ni'imar Allah, kuma ya yi masa uƙuba a kanta.

Suratul A'araf (31-32)

*يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ خُذُواْ زِينَتَكُمۡ عِندَ كُلِّ مَسۡجِدٖ وَكُلُواْ وَٱشۡرَبُواْ وَلَا تُسۡرِفُوٓاْۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُسۡرِفِينَ ٣١ قُلۡ مَنۡ حَرَّمَ زِينَةَ ٱللَّهِ ٱلَّتِيٓ أَخۡرَجَ لِعِبَادِهِۦ وَٱلطَّيِّبَٰتِ مِنَ ٱلرِّزۡقِۚ قُلۡ هِيَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا خَالِصَةٗ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ٣٢

31. Ya ku 'yan'adam, ku yi adonku a wurin kowane masallaci, ku ci, kuma ku sha, amma kada ku yi almubazzaranci. Lalle Shi (Allah) ba ya son masu almubazzaranci.

32. Ka ce: "Wane ne ya haramta kayan ado na Allah waɗanda (Allah) Ya fitar domin bayinsa da kuma daɗaɗan abubuwa na arziki?" Ka ce: "Waɗannan abubuwa na waɗanda suka yi imani ne a nan duniya, kuma nasu ne a keɓance a ranar lahira." Kamar haka ne Muke rarrabe ayoyi ga mutanen da suke da sani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar 'yan'adam da su sa kyakkyawar sutura, mai rufe tsiraici lokacin shiga masallaci domin yin salla, kuma su ci su sha daga abin da Allah ya halatta musu, kada kuma su yi almubazzaranci da abinci ko da abin sha ko ta hanyar barin abin da yake halal zuwa ga wanda ba halal ba ne, domin Allah ba ya son masu almubazzaranci.
Wannan ayar ta sauka ne a kan mushirikai masu yin ɗawafi tsirara suna cewa, wai bai dace su bauta wa Allah da tufafin da suke yin saɓo da su ba. Sai ya zamana duk ƙabilun Larabawa tsirara suke yin ɗawafi, in ban da Kuraishawa su ne kaɗai suke yin ɗawafi da tufafinsu, kuma su ne suke ara wa mutane tufafin da za su yi ɗawafi da su, namiji ya ara wa ɗan'uwansa namiji, mace ta ara wa mace 'yar'uwarta; wanda bai samu mai ba shi aro ba kuwa sai ya yi ɗawafi tsirara haihuwar uwarsa. Sai Allah ya rushe wannan mummunar al'adar, ya umarce su da sanya tufafinsu a lokacin da suka shiga ibada a kowane wurin ibada.

An karɓo daga Abu Hurairata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Annabi (ﷺ) ya shugabantar da Abubakar a aikin hajji (wato Amirul hajji) wanda aka yi kafin hajjin ban-kwana, ya umarce shi da ya fita a

ranar Idi ya sanar da mutane cewa, daga wannan she ƙarar kada wani mushiriki ya sake zuwa aikin hajji, kuma kada wani mutum ya ƙara yin ɗawafi a Ɗakin Ka'aba tsirara." [Bukhari #1622, da Muslim #1347].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya ƙalubalanci jahilan Larabawa masu yin ɗawafi tsirara suna haramta wa kansu abin da Allah ya halatta musu, cewa, wane ne ya haramta kayan sawa na ado da Allah ya hore wa bayinsa? Kuma wane ne ya haramta musu daɗaɗan abubuwa da Allah ya arzuta su da su? Ya kuma tabbatar musu cewa, kayan sawa na ado da daɗaɗan abubuwa na muminai ne a nan duniya, kuma kafirai ma suna tarayya da su wajen cin moriyarsu, amma a lahira za su zama na muminai ne su kaɗai. Da haka Allah yake bayanin ayoyinsa daki-daki ga mutanen da suka san gaskiya kuma suna yarda da ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya ambaci abubuwa waɗanda duk shari'o'in da ya saukar sun haɗu a kan haramcinsu, haramci kuma na dindindin, babu wani lokaci da za a halatta su, amma ban da mushe da jini da naman alade da makamantansu, waɗanda akan halatta su yayin larura.

2. An fara da bayanin abin da aka haramta shi don ƙaran-kansa, watau munanan ayyuka na sarari da na ɓoye, sai kuma aka ambaci wanda ya fi shi muni, wato saɓo da zalunci ba da wani haƙƙi ba, sai kuma aka je ga wanda ya ɗara su muni, wato yin shirka da Allah, sai aka je ga mafi munin cikinsu, wato yi wa Allah ƙarya. Duk waɗannan abubuwa sanadiyyarsu shi ne yi wa Allah ƙarya da jingina masa abin da bai kamace shi ba, da canza addininsa da tabbatar da abin da ya kore, ko kuma kore abin da ya tabbatar, da sauran ayyukan da suka danganci saɓon Allah da bidi'a da shirka.

Suratul A'araf (33-34)

قُلْ إِنَّمَا حَرَّمَ رَبِّيَ ٱلْفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنْهَا وَمَا بَطَنَ وَٱلْإِثْمَ وَٱلْبَغْىَ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَأَن تُشْرِكُوا۟ بِٱللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ سُلْطَٰنًا وَأَن تَقُولُوا۟ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٣٣﴾ وَلِكُلِّ أُمَّةٍ أَجَلٌ ۖ فَإِذَا جَآءَ أَجَلُهُمْ لَا يَسْتَـْٔخِرُونَ سَاعَةً وَلَا يَسْتَقْدِمُونَ ﴿٣٤﴾

33. Ka ce, "Ubangijina kawai Ya haramta munanan ayyuka na sarari da na ɓoye da saɓo da cutar wani ba da haƙƙi ba, kuma (Ya haramta) ku haɗa Allah da wani, irin abin da bai saukar da wani dalili a kai ba, kuma (Ya haramta) ku faɗi wani abu game da Allah wanda ba ku sani ba."

34. Kuma kowace al'umma tana da lokaci ƙayyadajje; don haka idan ajalinsu ya zo, ba za a yi musu jinkirin sa'a ɗaya ba; ba kuma za a gaggauta musu ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa mushrikai cewa, abin da kawai ya hana shi ne aikata munanan ayyuka na sarari da na ɓoye da duk wani saɓon Allah wanda ya keɓanci mai aikata shi da zalunci ba da wani haƙƙi ba, kuma ya haramta a haɗa shi da wani wajen bauta, abin da babu wata hujja ta yin haka. Haka kuma Allah ya haramta yin magana ba da ilimi ba a jingina ta da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wata al'umma da take ƙaryata manzonta tana da wani ƙayyadajjen lokacin da azaba za ta sauko mata, wanda idan lokacin ya zo to za su halaka nan take, ba tare da an jinkirta musu daidai da sa'a ɗaya ba, kuma ba za a gaggauto musu da azabar kafin zuwan lokacinta ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko manzanninsa daga jinsin mutane don yanke musu hanzari, kuma su samu nutsuwar sauraren su, su fahimce su.

2. Hikimar aiko da manzanni ita ce don ɗan'adam ya samu bin dokokin Allah, ya gyara rayuwarsa ta duniya da lahira.

3. Masu dawwama a cikin wutar Jahannama su ne kafirai kaɗai, ban da muminai masu saɓo; su ko an saka su cikinta, daga ƙarshe za a fitar da su zuwa Aljanna.

4. Akwai wasu mala'iku da Allah yake haɗa Mala'ikan Mutuwa da su domin karɓar ran bayinsa.

5. Aljannu su ma an aiko musu mazannin da suka gabata, an umarce su da aiki da shari'o'insu. Annabi (ﷺ) kuma an aiko shi ne ga mutane da aljannu gaba ɗaya.

6. Za a saka kafiran aljannu ma a cikin wutar Jahannama.

Suratul A'araf (35-39)

يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ إِمَّا يَأۡتِيَنَّكُمۡ رُسُلٞ مِّنكُمۡ يَقُصُّونَ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتِي فَمَنِ ٱتَّقَىٰ وَأَصۡلَحَ فَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٣٥ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَٱسۡتَكۡبَرُواْ عَنۡهَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٣٦ فَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوۡ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦٓۚ أُوْلَٰٓئِكَ يَنَالُهُمۡ نَصِيبُهُم مِّنَ ٱلۡكِتَٰبِۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَتۡهُمۡ رُسُلُنَا يَتَوَفَّوۡنَهُمۡ قَالُوٓاْ أَيۡنَ مَا كُنتُمۡ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ قَالُواْ ضَلُّواْ عَنَّا وَشَهِدُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ أَنَّهُمۡ كَانُواْ كَٰفِرِينَ ٣٧ قَالَ ٱدۡخُلُواْ فِيٓ أُمَمٖ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِكُم مِّنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِ فِي ٱلنَّارِۖ كُلَّمَا دَخَلَتۡ أُمَّةٞ لَّعَنَتۡ أُخۡتَهَاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا ٱدَّارَكُواْ فِيهَا جَمِيعٗا قَالَتۡ أُخۡرَىٰهُمۡ لِأُولَىٰهُمۡ رَبَّنَا هَٰٓؤُلَآءِ أَضَلُّونَا فَـَٔاتِهِمۡ عَذَابٗا ضِعۡفٗا مِّنَ ٱلنَّارِۖ قَالَ لِكُلّٖ ضِعۡفٞ وَلَٰكِن لَّا تَعۡلَمُونَ ٣٨ وَقَالَتۡ أُولَىٰهُمۡ لِأُخۡرَىٰهُمۡ فَمَا كَانَ لَكُمۡ عَلَيۡنَا مِن فَضۡلٖ فَذُوقُواْ ٱلۡعَذَابَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡسِبُونَ ٣٩

35. Ya ku 'yan'adam, idan har manzanni suka zo muku daga cikinku, suna ƙaranta muku ayoyina, to duk wanda ya yi taƙawa, kuma ya kyautata aiki, to babu jin tsoro tare da su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

36. Waɗanda kuwa suka ƙaryata ayoyinmu, kuma suka yi girman kai gare su, waɗannan su ne ma'abota wuta; suna masu dawwama a cikinta.

37. To wa ya fi wanda ya yi wa Allah ƙarya zalunci, ko ya ƙaryata ayoyinsa? Waɗannan rabonsu da aka rubuta a cikin littafi zai same su; har ya zuwa lokacin da manzannimu za su zo su karɓi ransu, sai su ce: "Ina waɗanda kuka kasance kuna kira ba Allah ba?" Sai su ce: "Sun ɓace mana." Kuma za su ba da shaida a kansu cewa, lalle su sun kasance kafirai.

38. Sai Ya ce: "Ku shiga cikin jerin al'ummomin da suka shuɗe kafinku na aljannu da mutane a cikin wuta." Ko da yaushe wata al'umma ta shiga (wutar) sai ta la'anci 'yar'uwarta; har sai lokacin da suka haɗu a cikinta gaba ɗaya, sai na ƙarshensu su ce wa na farkonsu: "Ya Ubangijinmu, waɗannan ne suka

ɓatar da mu, don haka Ka ninka musu azabar wuta.” Sai Ya ce: “Kowanne yana da ninki, sai dai ku ba ku sani ba ne.”

39. Sai kuma na farkonsu su ce wa na ƙarshensu: “Ai ba ku da wani fifiko a kanmu; to ku ɗanɗani azaba saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa ‘yan’adam cewa, idan manzanni daga cikin jinsinsu na mutane suka zo musu, suna ƙaranta musu ayoyin littafinsa, to duk wanda ya ji tsoron Allah, ya yi kyakkyawan aiki, ya bar abin da aka haramta masa, to waɗannan babu wani tsoro tare da su game da abin da za su sadu da shi bayan mutuwarsu, kuma babu wani baƙin ciki da za su yi game da abin da za su bari a nan duniya. Amma waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah, suka nuna girman kai na ƙin yarda da su ko aiki da su, to waɗannan ‘yan wuta ne, za su shige ta su yi ta zama a cikinta har abada.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu wani babban azzalumi da ya kai wanda ya ƙirƙiri ƙarya ya jingina wa Allah ko ya ƙaryata ayoyin da ya saukar; to waɗannan rabonsu da aka rubuta musu a Lauhul Mahfuz na arziki da ayyuka da shekaru da abin da zai same su na alheri ko na sharri, duk wannan zai same su kamar yadda aka rubuta musu shi, har zuwa lokacin da mala’ikun mutuwa za su zo karɓar rayukansu. To a sannan ne mala’iku za su tambaye su, ina abubuwan da suka bauta wa ba Allah ba? Sai su amsa musu cewa, ai sun ɓace musu; su yi iƙirari da kansu cewa su sun kasance kafirai ne.
Sai daga nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su shiga cikin ayarin kafiran sauran al’ummomi da suka gabace su na aljanu da mutane. Sai gaba ɗayansu su shiga wutar Jahannama. To duk sa’adda wata al’umma ta shiga wutar kuma, sai ta la’anci ‘yar’uwarta, har sai na farkonsu da na ƙarshensu duk sun tattara a wuta, sai na ƙarshen su ce wa na farkon: “Ya Ubangijinmu, waɗannan su ne muka bi a duniya, suka ɓatar da mu daga bin hanyarka; to ka yi musu azabar wuta ninkin tamu!” Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da amsa cewa: “Kowane daga cikinku za a ninka masa azabarsa, sai dai ku ba ku sani ba ne.”
Sai na farkonsu su ce wa na ƙarshensu: “Ba ku fi mu da komai ba.” Sai Allah ya faɗa musu gaba ɗayansu: “Ku ɗanɗani azaba saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa.” Wato na kafirci da saɓon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Munin girman kai, wanda shi ne ƙin gaskiya da wulaƙanta mutane.

2. Ana buɗe wa rayukan muminai ƙofofin sama ne bayan mutuwarsu, amma kafirai ba za a buɗe wa rayukansu ƙofofin sama ba bayan mutuwarsu, kuma ba za su shiga Aljanna ba har abada.

3. Munin sakamakon zalunci a ranar alƙiyama.

Suratul A’araf (40-41)

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَٱسۡتَكۡبَرُواْ عَنۡهَا لَا تُفَتَّحُ لَهُمۡ أَبۡوَٰبُ ٱلسَّمَآءِ وَلَا يَدۡخُلُونَ ٱلۡجَنَّةَ حَتَّىٰ يَلِجَ ٱلۡجَمَلُ فِي سَمِّ ٱلۡخِيَاطِۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٤٠ لَهُم مِّن جَهَنَّمَ مِهَادٞ وَمِن فَوۡقِهِمۡ غَوَاشٖۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلظَّٰلِمِينَ ٤١

40. Lalle waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, kuma suka yi girman kai gare su, ba za a buɗe musu ƙofofin sama ba, ba kuma za su shiga Aljanna ba, har sai raƙumi ya shige ta ƙofar allura. Kuma kamar haka ne Muke saka wa masu laifi.

41. Suna da shimfiɗa a cikin Jahannama daga samansu kuma akwai wuta mai lulluɓe su. Kuma kamar haka ne Muke saka wa azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, lalle waɗanda suka ƙaryata ayoyinsa, kuma suka yi girman kai gare su, to ayyukansu ba za su hau zuwa gare shi ba, ba kuma za a amsa musu addu'arsu ba, babu wata rahama ko albarka da za ta sauko musu. Yayin da kuma suka mutu, ba za a buɗe wa rayukansu ƙofofin sama ba, kuma ba za su shiga Aljanna ba har sai idan raƙumi zai shige ta ƙofar allura. To da irin wannan azaba ce Allah zai azabtar da kafirai masu laifi. Suna kuma da shimfiɗa ta wutar Jahannama a ƙarƙashinsu; daga samansu kuma akwai rufi na wuta ya lulluɓe su. Kamar haka ne Allah yake saka wa azzalumai.

Ya zo a cikin wani hadisi mai tsawo na Bara'u ɗan Azib (Allah ya ƙara masa yarda), Annabi (ﷺ) yana cewa: "Idan mala'ikun mutuwa suka fizge ran kafiri suka sa shi a cikin wani buhu yana ɗoyi fiye da kowane irin mushe a duniya, sai su yi sama da ran nasa. Duk sa'adda suka wuce da shi ta gaban wani taron mala'iku sai su ce: "Wannan wane rai ne mai muni haka?" Sai mala'ikun mutuwa su amsa musu cewa: "Wane ne ɗan wane." Su kira shi da mafi munin sunansa da ake kiran sa da shi a duniya, har sai sun isa sama ta farko da shi, sai su nemi a buɗe masa ƙofar, sai a ƙi buɗe masa." Sannan sai Annabi (ﷺ) ya ƙaranta wannan ayar: "Haƙiƙa waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, suka kuma yi girman kai game da su, ba za a buɗe musu ƙofofin sama ba, kuma ba za su shiga Aljanna ba har sai raƙumi ya shige ta kafar allura." [Ahmad #18534].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Aljanna tana tabbata ne ga waɗanda suka haɗa imani da aiki na ƙwarai.

2. Duk da girman ni'imar Aljanna, bawa yana samun ta ne da ayyuka marasa wahala, don haka Allah ya nuna ba ya ɗora wa mutum abin da ya fi ƙarfinsa.

3. Duk aikin wajibi idan ya fi ƙarfin mutum, to ya faɗi daga kansa.

4. Duk 'yan Aljanna suna samun ta ne da falalar Allah da ƙaramcinsa.

Suratul A'araf (42-43)

وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَا نُكَلِّفُ نَفۡسًا إِلَّا وُسۡعَهَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٤٢ وَنَزَعۡنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنۡ غِلّٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمُ ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَقَالُواْ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي هَدَىٰنَا لِهَٰذَا وَمَا كُنَّا لِنَهۡتَدِيَ لَوۡلَآ أَنۡ هَدَىٰنَا ٱللَّهُۖ لَقَدۡ جَآءَتۡ رُسُلُ رَبِّنَا بِٱلۡحَقِّۖ وَنُودُوٓاْ أَن تِلۡكُمُ ٱلۡجَنَّةُ أُورِثۡتُمُوهَا بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٤٣

42. Waɗanda kuwa suka yi imani, kuma suka aikata kyawawan ayyuka, ba ma ɗora wa rai, sai abin da zai iya, waɗannan su ne 'yan Aljanna, su masu dawwama ne a cikinta.

43. Muka kuma cire abin da yake cikin ƙirazansu na ƙullata, ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu; kuma za su ce: "Yabo ya tabbata ga Allah da Ya shiryar da mu ga wannan, kuma da ba za mu taɓa shiryuwa ba ba don Allah Ya shiryar da mu ba. Lalle haƙiƙa manzannin Ubangijinmu sun zo da gaskiya." Sai a kira su da cewa: "Waccan Aljannar an gadar muku da ita saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, ba ya ɗora wa kowane rai abin da ba zai iya ɗauka ba, saboda haka waɗanda suka yi imani kuma suka yi kyawawan ayyuka, su ne ‘yan Aljanna, masu zama a cikinta har abada.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya cire wa ‘yan Aljanna duk abin da yake cikin zukatansu na ƙullata da ƙiyayya da hassada, ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu.

An karɓo daga Abu Sa’id Alkhudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Muminai za su kuɓuta daga shiga wuta, sai a tara su a kan wata gada tsakanin Aljanna da wuta, sai a yi ramuwa tsakanin waɗanda aka zalunta da waɗanda suka zalunce su a duniya, har sai an tsaftace su daga duk wani laifi, sai a yi musu izini su shiga Aljanna. Na rantse da wanda ran Muhammadu yake hannunsa, sai ɗayansu ya fi gane gidansa na Aljanna fiye da yadda ya kasance yana gane gidansa na duniya.” [Bukhari #6535].

To yayin da muminai suka sami wannan ni’imar, za su yi wa Allah godiya da ya yi musu gam-da-katar da imani da kyawawan ayyuka waɗanda suka yi sanadiyyar shigarsu Aljanna, suka tabbatar da cewa, ba don Allah ya shiriyar da su ba, to da su ba za su iya shiryar da kansu ba, kuma suka bayyana cewa, manzannin Ubangijinsu sun zo musu da gaskiya. To sai a kira ‘yan Aljanna a faɗa musu cewa, an gadar musu da wannan Aljannar ne a sanadiyyar imaninsu da ayyukansu na ƙwarai.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk ɗan Aljanna zai gano masaukinsa ne a wuta, sai ya ce: “Kai, ba don Allah ya shirye ni ba!” Sai wannan ya zame masa abin godiya. Duk kuma ɗan wuta shi ma zai ga masaukinsa a Aljanna, sai ya ce: “Ina ma Allah ya shirye ni!” Sai wannan ya zame masa nadama.” [Nasa’i, *As-Sunan Al-Kubra* #11390, da Ahmad #10652].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Babu wani wanda aikinsa ne zai kuɓutar da shi.” Sahabbai suka ce; “Har kai ma ya Ma’aikin Allah?” Ya ce: “Har ni ma, sai dai kawai Allah ya lulluɓe ni da rahama.” [Bukhari #6463, da Muslim #2816].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Babu mutum ɗaya daga cikinku, face yana da gida biyu, gida a Aljanna da gida a wuta. Idan ya mutu ya shiga wuta, sai ‘yan Aljanna su gaje gidansa na Aljanna, wannan shi ne ma’anar faɗar Allah: “Waɗannan su ne masu gado.” *Suratul Mu’minun*, aya ta 10.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A ranar Alƙiyama kowa zai tabbatar da gaskiyar abin da annabawa da manzannin Allah suka ba da labarinsa.

2. Wasu kafiran ba sa taƙaita kafircinsu a kawunansu; sukan ma hana ma wasu mutane karɓar gaskiya, sannan kuma su yi ta ƙoƙarin sai sun ɓata sunan addinin Musulunci da Musulmi a idon duniya don a tsane su. To waɗannan kafircinsu ya yi muni ƙwarai da gaske.

3. Tabbatar da samuwar waɗanda ayyukansu masu kyau da marasa kyau za su daidaita a ranar alƙiyama; to waɗannan su ne ake tsare su a kan katangar La’arafi, don wannan ya zama wani horo ne a gare su kafin daga bisani a yi musu izinin shiga Aljanna.

4. Shuwagabannin kafirai da manyansu a duniya suna wulaƙanta raunanan Musulmi, suna yi musu izgili cewa, idan ma har da gaske akwai Aljanna a lahira, to su ne Allah zai sa a cikinta ba muminai ba. To a lahira za su gane kurensu lokacin da ganewar ba za ta amfane su da komai ba.

Suratul A'araf (44-49)

وَنَادَىٰٓ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِ أَصۡحَٰبَ ٱلنَّارِ أَن قَدۡ وَجَدۡنَا مَا وَعَدَنَا رَبُّنَا حَقّٗا فَهَلۡ وَجَدتُّم مَّا وَعَدَ رَبُّكُمۡ حَقّٗاۖ قَالُواْ نَعَمۡۚ فَأَذَّنَ مُؤَذِّنُۢ بَيۡنَهُمۡ أَن لَّعۡنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٤ ٱلَّذِينَ يَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَيَبۡغُونَهَا عِوَجٗا وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ كَٰفِرُونَ ٤٥ وَبَيۡنَهُمَا حِجَابٞۚ وَعَلَى ٱلۡأَعۡرَافِ رِجَالٞ يَعۡرِفُونَ كُلَّۢا بِسِيمَىٰهُمۡۚ وَنَادَوۡاْ أَصۡحَٰبَ ٱلۡجَنَّةِ أَن سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمۡۚ لَمۡ يَدۡخُلُوهَا وَهُمۡ يَطۡمَعُونَ ٤٦ ۞وَإِذَا صُرِفَتۡ أَبۡصَٰرُهُمۡ تِلۡقَآءَ أَصۡحَٰبِ ٱلنَّارِ قَالُواْ رَبَّنَا لَا تَجۡعَلۡنَا مَعَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٧ وَنَادَىٰٓ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأَعۡرَافِ رِجَالٗا يَعۡرِفُونَهُم بِسِيمَىٰهُمۡ قَالُواْ مَآ أَغۡنَىٰ عَنكُمۡ جَمۡعُكُمۡ وَمَا كُنتُمۡ تَسۡتَكۡبِرُونَ ٤٨ أَهَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ أَقۡسَمۡتُمۡ لَا يَنَالُهُمُ ٱللَّهُ بِرَحۡمَةٍۚ ٱدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ لَا خَوۡفٌ عَلَيۡكُمۡ وَلَآ أَنتُمۡ تَحۡزَنُونَ ٤٩

44. Kuma 'yan Aljanna za su kira 'yan wuta cewa: "Haƙiƙa mu kam mun samu abin da Ubangijinmu Ya yi mana alƙawari gaskiya ne, shin ku ma kun sami abin da Ubangijinku Ya yi muku alƙawari gaskiya ne?" Sai su ce, "E." Sai wani mai shela ya yi shela a tsakankaninsu cewa: "La'anar Allah ta tabbata a kan azzalumai.

45. "(Su ne) waɗanda suke hana mutane bin tafarkin Allah, kuma suke neman ya zama karkatacce, alhali su masu kafircewa ne da ranar lahira."

46. A tsakaninsu kuma akwai wani shamaki. Kuma a kan katangar La'arafi akwai waɗansu mazaje suna gane kowane (ɗan Aljanna da ɗan wuta) da alamominsu. Kuma sai su kira 'yan Aljanna cewa: "Amincin Allah ya tabbata a gare ku." (Lokacin) ba su shige ta ba, amma suna kwaɗayin (shigar ta).

47. Idan kuma an juyar da idanuwansu ɓangaren 'yan wuta sai su ce: "Ya Ubangijinmu, kada Ka sanya mu tare da mutane azzalumai."

48. Sai 'yan tozon La'arafi su kira waɗansu mazaje da suke gane su da alamominsu, sai su ce: "Taronku bai wadatar da ku da komai ba, da girman kan da kuka kasance kuna yi.

49. "Shin waɗannan ne waɗanda kuka riƙa yin rantsuwa cewa Allah ba zai sadar da rahamarsa zuwa gare su ba?" Ku shiga Aljanna babu wani tsoro tare da ku, kuma ba za ku yi baƙin ciki ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana tattaunawar da za ta gudana tsakanin 'yan Aljanna da 'yan wuta bayan kowa ya shiga makomarsa. 'Yan Aljanna za su kira 'yan wuta su faɗa musu cewa, su kam yanzu sun samu abin da Ubangijinsu ya yi musu alƙawarin zai ba su na sakamakon biyayyar da suka yi masa, gaskiya ne ya tabbata. To su ma 'yan wuta sun samu alƙawarin da Allah ya yi musu na azaba gaskiya ne ya tabbata? Sai su amsa musu da cewa, na'am haka ne sun gani. Daga nan sai mai shela ya yi shelar cewa, la'anar Allah ta tabbata ga kafirai azzalumai, waɗanda a duniya suka ƙi karɓar Musulunci, kuma suka hana mutane su karɓe shi, suka yi ta ɓata shi da yi masa ƙazafi don mutane su ƙyamace shi, kuma ba su yi imani da ranar lahira ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, akwai wani shamaki tsakanin 'yan wuta da 'yan Aljanna, shi ne wata doguwar katanga wadda a kanta za a tsare mutanen da kyawawan ayyukansu suka yi daidai da munanansu. Waɗannan mutane suna gane 'yan Aljanna da alamominsu, hakanan suna gane

‘yan wuta da alamominsu. Sai su kira ‘yan Aljanna, suna cewa, amincin Allah ya tabbata a gare su. Ga shi su ba su samu sun shiga Aljanna ba, amma suna kwaɗayin shiga cikinta.
Idan kuma aka juyar da ganinsu wajen ‘yan wuta, sai su roƙi Allah kada ya saka su cikin azzaluman mutane ‘yan wuta. Sai kuma su kirawo wasu shuwagabannin mushirikai waɗanda sun san su tun a duniya, kuma a nan ma lahira sun shaida su da alamominsu na ‘yan wuta, su faɗa musu cewa, yanzu dukiyar da suka tara a duniya da ‘ya’ya da mabiya da irin girman kan da suka riƙa nunawa ya kuwa amfane su da wani abu? Yanzu sai su dubi waɗannan raunanan mutanen da suka raina su a duniya, suna rantsuwa har da Allah cewa, Allah ba zai yi musu wata rahama ba, ga shi yanzu Allah ya shigar da su Aljanna, su kuma ya sa su wuta.

Daga nan sai a ce wa su waɗannan mutane na kan katangar La’arafi da ke tsakanin Aljanna da wuta, su shiga Aljanna babu wani tsoro tare da su, kuma ba wani ɓacin rai game da abin da suka bari a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa, ɗan’adam ba zai iya haƙura da ci da sha ba ko da kuwa yana cikin azaba ne.

2. Saboda bala’in zafi da kafirai suke ciki da ƙonewar duk wani abu da ke cikinsu, shi ya sa suka fara ambaton buƙatar ruwa sannan abinci.

3. Duk wanda ya bar Allah da koyarwarsa lokacin da yake cikin yalwa, to shi ma Allah zai watsar da shi lokacin da yake cikin tsanani yana buƙatar taimakonsa.

Suratul A’araf (50-53)

وَنَادَىٰٓ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ أَصۡحَٰبَ ٱلۡجَنَّةِ أَنۡ أَفِيضُواْ عَلَيۡنَا مِنَ ٱلۡمَآءِ أَوۡ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُۚ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ حَرَّمَهُمَا عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٥٠ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ دِينَهُمۡ لَهۡوٗا وَلَعِبٗا وَغَرَّتۡهُمُ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَاۚ فَٱلۡيَوۡمَ نَنسَىٰهُمۡ كَمَا نَسُواْ لِقَآءَ يَوۡمِهِمۡ هَٰذَا وَمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجۡحَدُونَ ٥١ وَلَقَدۡ جِئۡنَٰهُم بِكِتَٰبٖ فَصَّلۡنَٰهُ عَلَىٰ عِلۡمٍ هُدٗى وَرَحۡمَةٗ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٥٢ هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّا تَأۡوِيلَهُۥۚ يَوۡمَ يَأۡتِي تَأۡوِيلُهُۥ يَقُولُ ٱلَّذِينَ نَسُوهُ مِن قَبۡلُ قَدۡ جَآءَتۡ رُسُلُ رَبِّنَا بِٱلۡحَقِّ فَهَل لَّنَا مِن شُفَعَآءَ فَيَشۡفَعُواْ لَنَآ أَوۡ نُرَدُّ فَنَعۡمَلَ غَيۡرَ ٱلَّذِي كُنَّا نَعۡمَلُۚ قَدۡ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ وَضَلَّ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ ٥٣

50. Sai ‘yan wuta su kira ‘yan Aljanna cewa: “Ku kwararo mana ruwa ko abin da Allah Ya arzuta ku da shi.” Sai su ce: “Lalle Allah Ya haramta su ga kafirai.”

51. (Su ne) waɗanda suka ɗauki addininsu sharholiya da wargi, kuma rayuwar duniya ta ruɗe su. To a yau za Mu manta da su, kamar yadda suka manta da saduwa da wannan yinin nasu, da kuma jayayya da suka kasance suna yi da ayoyinmu.

52. Lalle haƙiƙa kuma Mun zo musu da littafin da Muka bayyana shi filla-filla bisa ilimi da shiriya da rahama ga mutanen da suke yin imani.

53. Shin akwai abin da suke jira ne in ba aukuwar abin da ya labarta ba?. Ranar da haƙiƙanin al’amarin zai zo, waɗanda a da suka manta da shi za su ce: “Haƙiƙa manzannin Ubangijinmu sun zo da gaskiya, shin

za mu samu masu ceto da za su cece mu, ko kuma za a mayar da mu, sai mu yi aiki ba irin wanda muka kasance muna yi ba?" Haƙiƙa sun yi hasarar rayuwarsu, kuma abin da suka kasance suna ƙirƙira ya ɓace musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa, 'yan wuta za su kirawo 'yan Aljanna, suna roƙon su da su kwararo musu ruwan sha daga gidan Aljanna, ko su sam musu kaɗan daga abincinsu wanda Allah ya ba su. Sai 'yan Aljanna su amsa musu da cewa, ai Allah ya haramta wa kafirai ruwan Aljanna da abincinta, saboda sun ɗauki addinin Allah da ake kiran su su ba da gaskiya da shi sun mayar da shi abin wasa da izgili, kuma rayuwar duniya ta ruɗe su har suka manta da lahira. To a ranar lahira Allah zai faɗa musu cewa, zai manta da su su yi ta shan azaba kamar yadda su ma a duniya suka manta da wannan rana ta lahira, kuma suka riƙa jayayya da ayoyin Allah.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah zai sadu da bawansa sai ya ce masa: "Wane, ashe ban girmama ka ba, na ba ka shugabanci, na ba ka aure, na hore maka dukiya ta dawakai da raƙuma, na bar ka kana shugabantar mutanenka, kana karɓar harajin rubu'in ganima daga hannunsu?" Sai ya ce: "Haka ne ya Ubangiji." Sai Allah ya ce masa: "To shin ka sakankance da cewa za ka gamu da ni?" Sai ya ce: "A'a." Sai Allah ya ce masa: "To zan manta da kai kamar yadda kai ma ka manta da ni." Sannan Allah ya sadu da bawansa na biyu, sai ya ce masa: "Wane, ashe ba na girmama ka ba, na ba ka shugabanci, na ba ka aure, na hore maka dukiya ta dawaki da raƙuma, na bar ka kana shugabantar mutanenka, kana karɓar harajin rubu'in ganima daga hannunsu?" Sai ya ce: "Haka ne ya Ubangiji." Sai Allah ya ce masa: "Shin ka sakankance da cewa za ka gamu da ni?" Sai ya ce: "A'a." Sai Allah ya ce: "To zan manta da kai kamar yadda kai ma ka manta da ni." [Muslim #2968].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa cewa, ya saukar wa waɗannan kafirai littafin Alƙur'ani wanda a cikinsa ya yi bayanin komai da ɗan'adam yake buƙatar ya sani dangane da addini da rayuwa filla-filla da ilimi da shiriya ga muminai, don kuma ya zama rahama gare su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin ƙarshen lamarin kafirai da cewa, shin yanzu akwai wani abu da kafirai suke jira in ban da aukuwar abin da Alƙur'ani ya ba da labarin zai auku na zuwan ranar alƙiyama da tsayuwa domin hisabi da shigarsu cikin azabar Allah da shigar 'yan Aljanna gidan Aljanna? To ranar da duk waɗannan abubuwa za su auku, kafirai da suka ƙi yin imani da Alƙur'ani da gaskiyar da ya zo da ita, za su yi nadama marar amfani, su riƙa cewa: A yau dai ga shi sun gane cewa, ashe manzannin Allah da gaskiya suka zo musu, amma sai suka ƙaryata su, to ko yanzu za su samu waɗanda za su cece su a wajen Ubangijinsu, ko kuma za a mayar da su duniya su yi aiki ba irin wanda suka yi a da ba na kafirci da saɓon Allah? Allah ya bayyana cewa, waɗannan kafirai sun tafka hasara ga kawunansu, kuma abin da suke riyawa a duniya cewa su abokan tarayya ne da Allah, a yau ga shi sun ɓace musu, ba su yi musu wani amfani ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da ikon ya halicci sammai da ƙasa da kalma ɗaya kuma a lokaci ɗaya, to amma sai ya halicce su a cikin kwana shida domin ya nuna wa bayinsa hikimar bin abubuwa a sannu a hankali da guje wa garaje cikin dukkan al'amuransu.

2. Allah mai girma da buwaya ya daidaita a kan Al'arshinsa daidaito wanda ya dace da girmansa.

3. Kasancewar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai ne ya yi halitta, to ya zama wajibi a bauta masa shi kaɗai, kuma shi kaɗai ne yake da haƙƙin shar'antawa da tsara dokoki na rayuwar ɗan'adam.

4. Kwaɗaitarwa a kan yin addu’a.

5. An fi son addu’ar ɓoye a kan ta sarari, saboda ta ɓoye ta fi nesa daga riya.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya son masu ƙetare iyaka wajen addu’a, kamar wanda zai roƙi Allah abin da ya saɓa sunnoninsa, kamar ya roƙi fika-fiki irin na tsuntsaye, ko abin da ya saɓa wa shari’a, kamar saɓon Allah ko zaluntar wani. Hakanan, ɗaga murya da ƙarfi ko rashin ƙasƙantar da kai yayin addu’ar yana daga cikin wuce gona da iri.

7. Ya wajaba bawa ya kai kokensa ga Allah game da abin da ya dame shi.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son bayinsa masu roƙon sa suna kai buƙatunsu gare shi.

9. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana yaɗa ɓarna a bayan ƙasa bayan an gyara ta. Babban gyara da Allah ya yi wa ƙasa kuwa shi ne aiko da Manzonsa Muhammadu (ﷺ) da addininsa wanda ya ƙunshi Tauhidi, wato bautar Allah shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba. Mafi girman laifi kuwa shi ne yin shirka da Allah da saɓa wa Manzonsa. Don haka tushen duk wani gyara a duniya dalilinsa shi ne Tauhidi, hakanan duk wata ɓarna a duniya sanadiyyarta yin shirka da Allah.

10. Bin umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da kauce wa haninsa kamar kana ganin sa shi ne ihsani, wato kyautayi. Duk wanda ya kyautata aikinsa tsakaninsa da Allah, to shi kuma zai yi masa rahama.

Suratul A’araf (54-56)

إِنَّ رَبَّكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ ۖ يُغْشِى ٱلَّيْلَ ٱلنَّهَارَ يَطْلُبُهُۥ حَثِيثًا وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ وَٱلنُّجُومَ مُسَخَّرَٰتٍۭ بِأَمْرِهِۦٓ ۗ أَلَا لَهُ ٱلْخَلْقُ وَٱلْأَمْرُ ۗ تَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٥٤﴾ ٱدْعُوا۟ رَبَّكُمْ تَضَرُّعًا وَخُفْيَةً ۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلْمُعْتَدِينَ ﴿٥٥﴾ وَلَا تُفْسِدُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ بَعْدَ إِصْلَٰحِهَا وَٱدْعُوهُ خَوْفًا وَطَمَعًا ۚ إِنَّ رَحْمَتَ ٱللَّهِ قَرِيبٌ مِّنَ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٥٦﴾

54. Lalle Ubangijinku shi ne Allah wanda Ya halicci sammai da ƙasa cikin kwanaki shida, sannan sai Ya daidaita a kan Al’arshi, Yana lulluɓe (duhun) dare da (hasken) yini, (kowannensu) yana neman sa (ɗan’uwansa) a gurguje, da rana da wata da taurari kuma abubuwan horewa ne da umarninsa. Haƙiƙa halitta da umarni nasa ne. Albarkatun Allah Ubangijin talikai sun yawaita.

55. Ku roƙi Ubangijinku kuna masu ƙasƙantar da kai, kuma a ɓoye. Lalle Shi ba ya son masu ƙetare iyaka.

56. Kuma kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan gyara ta, kuma ku bauta masa kuna masu tsoro da kwaɗayi. Lalle rahamar Allah a kusa take da masu kyautatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, shi ne wanda ya halicci sammai da ƙasa a cikin kwanaki shida, sannan ya daidaita a kan Al’arshi, daidaito wanda ya dace da shi. Yana rufe hasken rana da duhun dare, ya kuma rufe duhun dare da hasken rana; kowane ɗaya daga cikinsu yana neman ɗayan da gaggawa ba ya jinkiri. Kuma ya halicci rana da wata da taurari waɗanda ya hore su da al’amarinsa da ikonsa don amfanin halittarsa. Haƙiƙa ƙirƙirar halitta da ba da umarni da hani duka nasa ne shi kaɗai. Albarkatunsa sun yawaita a ko’ina, shi ne Ubangijin talikai.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mutane da su roƙe shi a cikin ƙasƙantar da kai da ɓoye addu'o'insu gare shi, ya nuna cewa, ba ya son masu wuce gona da iri a lokacin da suke yin addu'a.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Muna tare da Annabi (ﷺ) cikin wata tafiya, sai mutane suka riƙa ɗaga murya suna yin kabbara da ƙarfi, sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Ku sauƙaka wa kanku ya ku mutane, domin ba kurma ko wanda ba ya nan kuke kira ba; kuna kiran mai ji ne kuma makusanci, yana nan tare da ku." [Bukhari #2992, da Muslim #2704].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kashedi game da yaɗa ɓarna a bayan ƙasa bayan gyara ta, su kuma ji tsoron fushinsa da uƙubarsa, tare da kwaɗayin samun yardarsa da sakamakonsa. Rahamar Allah kuma tana kusa da masu kyautatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a kan yin tunani game da ni'imomin Allah da ɗaukar izina daga gare su.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin zukata lokacin da wahayinsa ya sauko gare su. Wahayi shi ne sinadarin rayuwar zukata kamar yadda ruwan sama yake sinadarin rayuwar ƙasa. A cikin zukatan bayi akwai lafiyayyar zuciya kyakkyawa wadda idan wahayi ya zo mata za ta karɓe shi, ta fahimce shi, ta yi aiki da shi, sai ka ga kyawawan halaye suna bayyana daga gare ta. Akwai kuma zuciya marar lafiya mummuna wadda babu wani alheri a cikinta, to wannan yayin da wahayi zai zo mata ba zai samu karɓuwa ba a wurinta, zai same ta mai bijirewa, sai ta zama kamar ruwan sama lokacin da ya sauka a kan ƙasar da take taɓo ce ko rairayi ko duwatsu; to ba zai yi mata wani tasiri ba, don haka ba za ta amfana da shi ba.

3. Fito da tsirrai daga ƙeƙasasshiyar ƙasa bayan ruwan sama ya sauka a kanta yana nuna wa ɗan'adam yadda Allah zai fitar da matattu daga ƙaburburansu yayin tashin alƙiyama.

4. Masu godiya ga Allah ne kaɗai masu amfanuwa da sauraron Alƙur'ani.

Suratul A'araf (57-58)

وَهُوَ ٱلَّذِى يُرۡسِلُ ٱلرِّيَٰحَ بُشۡرَۢا بَيۡنَ يَدَىۡ رَحۡمَتِهِۦۖ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَقَلَّتۡ سَحَابًا ثِقَالٗا سُقۡنَٰهُ لِبَلَدٖ مَّيِّتٖ فَأَنزَلۡنَا بِهِ ٱلۡمَآءَ فَأَخۡرَجۡنَا بِهِۦ مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِۚ كَذَٰلِكَ نُخۡرِجُ ٱلۡمَوۡتَىٰ لَعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ ٥٧ وَٱلۡبَلَدُ ٱلطَّيِّبُ يَخۡرُجُ نَبَاتُهُۥ بِإِذۡنِ رَبِّهِۦۖ وَٱلَّذِى خَبُثَ لَا يَخۡرُجُ إِلَّا نَكِدٗاۚ كَذَٰلِكَ نُصَرِّفُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَشۡكُرُونَ ٥٨

57. Kuma Shi ne Wanda yake aiko da iska don albishir kafin zuwan rahamarsa; har lokacin da ta ɗauko gizagizai masu nauyi (cike da ruwa), sai Mu kora shi ga wani gari matacce, sai Mu saukar da ruwa da shi, Mu kuma fitar da dukkan 'ya'yan itace a sanadiyyarsa. Kamar haka ne Muke fito da matattu don ku wa'azantu.

58. Wuri kuma mai kyau, tsironsa yana fitowa (kyakkyawa) da izinin Ubangijinsa. Wuri kuwa lalatacce (shukarsa) ba ta fita sai da kyar. Kamar haka ne Muke sarrafa ayoyi ga mutanen da suke yin godiya.
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tabbatar mana cewa, shi ne yake aiko da iska mai yin albishir da saukowar ruwan sama wanda rahama ne ga bayinsa. Har wannan iska ta ɗauko girgije mai nauyi cike da ruwa sai Allah ya kaɗa wannan girgijen zuwa ga wani gari matacce, wato wanda ya ƙeƙashe

saboda rashin samun ruwan sama, sai ya saukar da wannan ruwa a wannan gari, ya fitar da tsirrai da ‘ya’yan itatuwa da shi bayan fari ya lahanta shi. To kamar haka ne Allah yake fitar da matattu da ransu daga ƙaburburansu, kuma yana yin haka ne domin mutane su wa’azantu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ƙasar da take kyakkyawa shukarta tana fita da kyau da izinin Allah, amma mummunar ƙasa shukarta ba ta fitowa sai da ƙyar kuma marar amfani marar albarka. To kamar haka ne Allah yake bayyana ayoyi ga mutane masu godiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Farkon abin da yake wajaba a kan bawa shi ne sanin Tauhidi, wato bautar Allah shi kaɗai ba tare da an yi shirka da shi da kowa ba.

2. Mai kira zuwa ga Allah dole ne ya yi haƙuri da baƙaƙen maganganu da zai riƙa ji daga bakin maƙiyansa.

3. Duk manzannin Allah sun isar da saƙon da ya aiko su da shi, kuma sun yi wa mutanensu nasiha.

4. Annabi a cikin kowace al’umma ya fi kowa sanin Allah da haƙƙoƙinsa.

5. Mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun riƙa mamakin aiko da mutum a matsayin manzon Allah. Hakanan al’ummomin sauran annabawa da yawa suka ƙi karɓar gaskiya da hujjar cewa, wai Allah ba zai aiko mutum ba. Annabawa da manzanni su ma mutane ne, Allah ya zaɓe su ne ya yi musu wahayi.
6. Bawa yana yin ibada ne da kiyaye dokokin Allah domin tsammanin samun rahamar Allah.

Suratul A’araf (59-64)

لَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ فَقَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥٓۖ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ٥٩ قَالَ ٱلۡمَلَأٞ مِن
قَوۡمِهِۦٓ إِنَّا لَنَرَىٰكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٦٠ قَالَ يَٰقَوۡمِ لَيۡسَ بِي ضَلَٰلَةٞ وَلَٰكِنِّي رَسُولٞ مِّن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦١ أُبَلِّغُكُمۡ رِسَٰلَٰتِ رَبِّي وَأَنصَحُ لَكُمۡ
وَأَعۡلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٦٢ أَوَعَجِبۡتُمۡ أَن جَآءَكُمۡ ذِكۡرٞ مِّن رَّبِّكُمۡ عَلَىٰ رَجُلٖ مِّنكُمۡ لِيُنذِرَكُمۡ وَلِتَتَّقُواْ وَلَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٦٣
فَكَذَّبُوهُ فَأَنجَيۡنَٰهُ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥ فِي ٱلۡفُلۡكِ وَأَغۡرَقۡنَا ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمًا عَمِينَ ٦٤ لَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ فَقَالَ يَٰقَوۡمِ
ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥٓۖ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ٥٩ قَالَ ٱلۡمَلَأٞ مِن قَوۡمِهِۦٓ إِنَّا لَنَرَىٰكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٦٠ قَالَ
يَٰقَوۡمِ لَيۡسَ بِي ضَلَٰلَةٞ وَلَٰكِنِّي رَسُولٞ مِّن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦١ أُبَلِّغُكُمۡ رِسَٰلَٰتِ رَبِّي وَأَنصَحُ لَكُمۡ وَأَعۡلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٦٢
أَوَعَجِبۡتُمۡ أَن جَآءَكُمۡ ذِكۡرٞ مِّن رَّبِّكُمۡ عَلَىٰ رَجُلٖ مِّنكُمۡ لِيُنذِرَكُمۡ وَلِتَتَّقُواْ وَلَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٦٣ فَكَذَّبُوهُ فَأَنجَيۡنَٰهُ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥ فِي
ٱلۡفُلۡكِ وَأَغۡرَقۡنَا ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمًا عَمِينَ ٦٤

59. Lalle haƙiƙa Mun aiko Nuhu zuwa ga mutanensa, sai ya ce: “Ya ku mutanena, ku bautata wa Allah, ba ku da wani abin bautawa da gaskiya sai Shi, lalle ni ina ji muku tsoron azabar wani yini mai girma.”

60. Sai manyan gari cikin mutanensa suka ce: “Lalle mu tabbas muna ganin kana cikin ɓata mabayyani.”

61. Sai ya ce: “Ya ku mutanena, babu wata ɓata tare da ni, sai dai ni Manzo ne daga Ubangijin halittu.”

62. “Ina isar muku da saƙonnin Ubangijina, ina kuma yi muku nasiha, na kuma san abin da ba ku sani ba daga Allah.

63. “Shin kun yi mamaki ne don wa’azi ya zo muku daga Ubangijinku, ta kan harshen wani mutum cikinku, don ya gargaɗe ku, don ku kuma kiyaye dokokin Allah domin a ji ƙan ku?”

64. Sai suka ƙaryata shi, sai Muka tserar da shi da waɗanda suke tare da shi, a cikin jirgin ruwa, kuma Muka dulmiyar da waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu. Lalle su sun kasance mutane makafi.

A waɗannan ayoyi da wasu masu zuwa nan gaba Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin annabawan da ya aiko wa al’ummomin da suka gabata. Daga cikin amfanin kawo waɗannan labarai shi ne:

1. Ba da labarin cewa, faɗa da gaskiya da bijire wa annabawa ba daga al’ummar Annabi Muhammadu (ﷺ) aka fara shi ba; wannan wata daɗaɗɗiyar al’ada ce a tarihin rayuwar ɗan’adam. A nan akwai rarrashin Annabi (ﷺ) da haƙurƙurtar da shi.

2. Bayanin cewa, ƙarshen duk wasu masu girman kai da faɗa da gaskiya shi ne taɓewa da la’anar Allah da ke tabbata a kansu da hasarar duniya da ta lahira. Amma masu gaskiya da aiki da ita ƙarshen al’amarinsu shi ne samun nasara da arzikin duniya da na lahira.

3. Bayani a kan cewa, Allah yana iya jinkirta wa masu laifi, amma ba zai ƙyale su ba sai ya saukar musu da azabarsa.

4. Waɗannan labaran suna ƙara tabbatar da annabcin Annabi (ﷺ), domin kasancewarsa ba ya rubutu kuma ba ya ƙaratu, kuma ba shi da wani malami mutum ko aljan, to sai ga shi ana samun waɗannan labarai daga wajensa, wannan babu shakka ya tabbatar da cewa, wahayi yana zo masa ne daga Allah.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara bayyana mana cewa, ya aiko da Manzonsa Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga mutanensa domin ya kirawo su zuwa ga bautar Allah shi kaɗai da barin bauta wa wani ba shi ba. Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana wa mutanensa haka, ya kuma ja hankalinsu da su ji tsoron ranar lahira, domin kuwa yana jiye musu tsoron azabar wannan ranar. To amma sai shugabanni masu girman kai a cikin mutanensa suka ce masa, su fa lalle suna ganin sa yana cikin wani ɓata ne bayyananne. Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ce musu, shi fa ba ya cikin wani ɓata; ya zo ne kawai ya yi kiran su zuwa ga Tauhidi da barin shirka, kuma Allah Ubangijin talikai ne ya aiko shi don ya isar musu da wannan saƙo, ya kuma yi musu nasiha, kuma shi ya san abin da su ba su sani ba, don shi ana yi masa wahayi ne, su kuma ba a yi musu. Ya sake nuna musu cewa, bai kamata su yi mamaki ba don an aiko musu da wani mutum daga cikinsu yana gargaɗin su yana tsoratar da su azabar Allah idan sun kafirce masa, yana horon su da su ji tsoron Allah su bi shi don su gamu da rahamarsa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da mu cewa, mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ƙaryata shi, to amma sai ya saukar musu da azabar ruwan Ɗufana wanda ya halaka su, kuma ya kuɓutar da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanen da suke tare da shi a cikin jirgin ruwa. Allah ya bayyana cewa, mutanen Annabi Nuhu sun makance don haka sun kasa ganin gaskiya su bi ta, sai suka cancanci wannan azabar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawa zaɓaɓɓun mutane ne masu cikakken hankali da haƙuri. Wannan ne ya sa Annabi Nuhu da Annabi Hudu ba su mayar wa mutanensu da baƙar magana irin tasu ba yayin da suka jefe su da ɓata da wauta.

2. Wajibi ne ga bawa ya riƙa tuna ni'imomin da Allah ya yi masa, yana gode masa a kansu.

3. Godiya ga ni'imomin Allah ita ce sababin samun rabauta da arziƙi na duniya da lahira.

4. Ba koyaushe ne aikin iyaye yake zama abin koyi ba, sai ya dace da koyarwar shari'a.

5. Duk wani abu na bautar Allah dole ne a same shi ta hanyar wahayi, ba ra'ayi da kwaikwayon wasu ba.

6. Halaccin kiran kafiri makusanci da sunan 'ɗan'uwa'.

7. Aƙidar da Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo da ita ita ce irin aƙidar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da sauran annabawa da suka zo bayansa, wato kaɗaita Allah da bauta da guje wa haɗa shi da komai, domin wannan shi ne babbar manufar aiko da annabawa da manzanni.

8. Maganganun mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) duk sun yi kama da juna wajen ƙaryata saƙon Allah, domin ɓata daga kan hanyar Allah abu ɗaya ne, don haka manufofinsu guda ne.

9. Ba a zaɓar annabawa da manzanni sai masu hankali da hikima da haƙuri da gaskiya, domin da haka ne hujjar Allah za ta tsaya a kan mutane.

10. Babu laifi ga wanda aka tuhume shi da ɓata masa suna ya kare kansa ta hanyar faɗar siffofinsa na gaskiya; wannan ba ya daga cikin yabon kai da aka hana.

Suratul A'araf (65-72)

*وَإِلَىٰ عَادٍ أَخَاهُمْ هُودًا ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ ۖ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿٦٥﴾ قَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَوْمِهِۦٓ إِنَّا لَنَرَىٰكَ فِى سَفَاهَةٍ وَإِنَّا لَنَظُنُّكَ مِنَ ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿٦٦﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ لَيْسَ بِى سَفَاهَةٌ وَلَٰكِنِّى رَسُولٌ مِّن رَّبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٦٧﴾ أُبَلِّغُكُمْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّى وَأَنَا۠ لَكُمْ نَاصِحٌ أَمِينٌ ﴿٦٨﴾ أَوَعَجِبْتُمْ أَن جَآءَكُمْ ذِكْرٌ مِّن رَّبِّكُمْ عَلَىٰ رَجُلٍ مِّنكُمْ لِيُنذِرَكُمْ ۚ وَٱذْكُرُوٓاْ إِذْ جَعَلَكُمْ خُلَفَآءَ مِنۢ بَعْدِ قَوْمِ نُوحٍ وَزَادَكُمْ فِى ٱلْخَلْقِ بَصْۜطَةً ۖ فَٱذْكُرُوٓاْ ءَالَآءَ ٱللَّهِ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴿٦٩﴾ قَالُوٓاْ أَجِئْتَنَا لِنَعْبُدَ ٱللَّهَ وَحْدَهُۥ وَنَذَرَ مَا كَانَ يَعْبُدُ ءَابَآؤُنَا ۖ فَأْتِنَا بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٧٠﴾ قَالَ قَدْ وَقَعَ عَلَيْكُم مِّن رَّبِّكُمْ رِجْسٌ وَغَضَبٌ ۖ أَتُجَٰدِلُونَنِى فِىٓ أَسْمَآءٍ سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ وَءَابَآؤُكُم مَّا نَزَّلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ ۚ فَٱنتَظِرُوٓاْ إِنِّى مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُنتَظِرِينَ ﴿٧١﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥ بِرَحْمَةٍ مِّنَّا وَقَطَعْنَا دَابِرَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا ۖ وَمَا كَانُواْ مُؤْمِنِينَ ﴿٧٢﴾

65. Kuma Mun aika wa Adawa ɗan'uwansu Hudu. Ya ce: "Ya ku mutanena, ku bautata wa Allah, ba ku da wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Shin ba za ku kiyaye dokokin Allah ba?"

66. Sai manyan gari waɗanda suka kafirce cikin mutanensa suka ce: "Lalle mu tabbas muna ganin ka kana cikin wauta, kuma lalle mu tabbas muna zaton kai kana cikin maƙaryata.

67. Sai ya ce: "Ya ku mutanena, babu wata wauta a tare da ni, sai dai ni kawai Manzo ne daga Ubangijin talikai.

68. "Ina isar muku da saƙonnin Ubangijina, kuma ni mai nasiha ne a gare ku, amintacce.

69. "Shin mamaki kuke yi wa'azi ya zo muku daga Ubangijinku a kan (harshen) wani mutum daga cikinku don ya gargaɗe ku? Kuma ku tuna yayin da Ya sa kuka zama masu maye gurbi bayan wucewar mutanen Nuhu, kuma Ya ƙara muku girman halitta; don haka ku tuna ni'imomin Allah, don ku rabauta."

70. Sai suka ce: "Yanzu ka zo mana ne don mu bauta wa Allah Shi kaɗai, kuma mu ƙyale abin da iyayenmu suka kasance suna bautata wa? To ka kawo mana abin da kake yi mana alƙawarinsa idan ka kasance cikin masu gaskiya."

71. Sai ya ce: "Haƙiƙa azaba da fushi daga Ubangijinku sun faɗa a kanku. Yanzu kwa riƙa jayayya da ni a kan waɗansu sunaye da ku ne kuka ƙago su da iyayenku, alhalin Allah bai saukar da wata hujja a kansu ba? To ku jira (ku gani), lalle ni ma ina nan cikin masu jira tare da ku."

72. Sai Muka tserar da shi, da waɗanda suke tare da shi da rahamarmu, Muka kuma tumɓuke tushen waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu; kuma ba su kasance muminai ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin Adawa mutanen Annabi Hudu. Adawa wasu ƙabilu ne na Larabawa waɗanda suka zauna a ƙasar *Al-Ahƙaf*, kudancin tsibirin Larabawa, arewa da *Hadaramaut* ta ƙasar Yaman, kuma gabas da ƙasar Oman. A yanzu garuruwansu kango ne, babu wani ɗan'adam da yake rayuwa a wurin. Allah ya aiko musu ɗaya daga cikinsu shi ne Annabi Hudu domin ya yi kiran su zuwa bauta wa Allah shi kaɗai ba tare da yi masa shirka ba, ya nusar da su a kan su ji tsoron Ubangijinsu da azabarsa da fushinsa, amma sai shugabanninsu masu girman kai suka ce masa, su fa lalle suna ganin sa wani wawa ne marar cikakken hankali, kuma ma lalle suna zaton shi maƙaryaci ne. Sai Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya mayar musu da martani cewa, shi ba ya da wata wauta ko ƙarancin hankali; shi Manzo ne da Allah ya aiko musu shi don ya isar musu da saƙon Ubangijinsu, kuma shi mai nasiha ne amintacce a gare su.
Sai kuma Annabi Hudu ya nuna musu cewa, bai kamata su riƙa mamakin an aiko musu da wani mutum daga cikinsu domin ya tsoratar da su uƙubar Ubangijinsu gare su saboda kafircinsu ba. Kuma su tuna ni'imar da Allah ya yi musu yayin da ya sanya su suka maye gurbin mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan ya halaka su, sannan ya ƙara musu tsawo da ƙarfin jiki. Don haka su riƙa tuna ni'imomin Allah da ya yi musu don su sami rabauta duniya da lahira.
To amma duk da irin wannan jan hankalin da Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mutanensa, sai suka bijire wa kiransa, suka nuna masa cewa, yaya za a yi su bar abin da iyayensu suke bauta wa? Sai dai Annabi Hudu ya zo musu da azabar da yake tsorata su da ita idan har shi mai gaskiya ne. Sai Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ce musu, tabbas azabar Allah da fushinsa sun tabbata a kansu babu makawa, ya nuna musu mamakinsa da har suke jayayya da shi a kan wasu gumaka nasu waɗanda su da iyayensu ne suka raɗa musu suna suna bauta musu, babu wata hujja daga

Allah da suke iya nunawa a kan bautar su. Don haka su jira azabar Allah da za ta auka musu, shi ma zai jira tare da su.
Daga ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya tserar da Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka ba da gaskiya da shi, sannan ya halaka waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah, ba su yi imani da Annabi Hudu ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ya wajaba bawa ya riƙa tuna ni'imomin Allah yana gode masa, ya guji yin butulci da kafirci domin hakan yana jawo fushin Allah da azabarsa.

2. Imani da Allah yana ba da ƙarfi da nutsuwa a cikin zukata, don haka duk wata barazanar azzalumai ba za ta firgita muminai ba.
3. Abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ƙarfafar annabawa da shi na mu'ujiza aikinsa ne ba su ne suka yi wa kansu ba; shi ne yake ganin dama ya yi musu. Hakanan ƙaramar salihai da waliyyai ba su ne suke yi wa kawunansu ba, falala ce daga Alalh (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Halaccin gina manyan gidaje ga waɗanda Allah ya hore musu halin yin haka. Kuma wannan ni'ima ce daga ni'imomin Allah da ya wajaba a gode masa a kanta.

5. Girman kai yana hana mutum yarda da gaskiya, ya haifar masa wulaƙanta mutane.

6. Idan mutum ɗaya ya aikata wani laifin da mutane masu yawa ne suka shirya shi ko suka yarda da shi, to kamar su duka ne suka aikata wannan laifin, kuma uƙubarsa za ta shafe su ne gaba ɗaya.

Suratul A'araf (73-79)

وَإِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمْ صَٰلِحًا ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥ ۖ قَدْ جَآءَتْكُم بَيِّنَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ ۖ هَٰذِهِۦ نَاقَةُ ٱللَّهِ لَكُمْ ءَايَةً ۖ
فَذَرُوهَا تَأْكُلْ فِىٓ أَرْضِ ٱللَّهِ ۖ وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوٓءٍ فَيَأْخُذَكُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٧٣﴾ وَٱذْكُرُوٓا۟ إِذْ جَعَلَكُمْ خُلَفَآءَ مِنۢ بَعْدِ عَادٍ وَبَوَّأَكُمْ فِى
ٱلْأَرْضِ تَتَّخِذُونَ مِن سُهُولِهَا قُصُورًا وَتَنْحِتُونَ ٱلْجِبَالَ بُيُوتًا ۖ فَٱذْكُرُوٓا۟ ءَالَآءَ ٱللَّهِ وَلَا تَعْثَوْا۟ فِى ٱلْأَرْضِ مُفْسِدِينَ ﴿٧٤﴾ قَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ
ٱسْتَكْبَرُوا۟ مِن قَوْمِهِۦ لِلَّذِينَ ٱسْتُضْعِفُوا۟ لِمَنْ ءَامَنَ مِنْهُمْ أَتَعْلَمُونَ أَنَّ صَٰلِحًا مُّرْسَلٌ مِّن رَّبِّهِۦ ۚ قَالُوٓا۟ إِنَّا بِمَآ أُرْسِلَ بِهِۦ مُؤْمِنُونَ ﴿٧٥﴾ قَالَ
ٱلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوٓا۟ إِنَّا بِٱلَّذِىٓ ءَامَنتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ﴿٧٦﴾ فَعَقَرُوا۟ ٱلنَّاقَةَ وَعَتَوْا۟ عَنْ أَمْرِ رَبِّهِمْ وَقَالُوا۟ يَٰصَٰلِحُ ٱئْتِنَا بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ مِنَ
ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٧٧﴾ فَأَخَذَتْهُمُ ٱلرَّجْفَةُ فَأَصْبَحُوا۟ فِى دَارِهِمْ جَٰثِمِينَ ﴿٧٨﴾ فَتَوَلَّىٰ عَنْهُمْ وَقَالَ يَٰقَوْمِ لَقَدْ أَبْلَغْتُكُمْ رِسَالَةَ رَبِّى وَنَصَحْتُ لَكُمْ
وَلَٰكِن لَّا تُحِبُّونَ ٱلنَّٰصِحِينَ ﴿٧٩﴾

73. Zuwa ga Samudawa kuwa Mun aika ɗan'uwansu Salihu. Ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; haƙiƙa hujja ta zo muku daga Ubangijinku. Wannan kuma taguwar Allah aya ce a gare ku; don haka ku ƙyale ta ta ci a bayan ƙasar Allah; kuma kar ku taɓa ta da wani mugun abu, sai wata azaba mai raɗaɗi ta shafe ku.

74. "Kuma ku tuna lokacin da Ya sanya ku kuka zama masu maye gurbi bayan Adawa, kuma Ya zaunar da ku a bayan ƙasa, kuna yin benaye a wurarenta masu taushi, kuma kuna sassaƙa gidaje a duwatsu; don haka ku tuna ni'imomin Allah, kada kuma ku yi ɓarna a bayan ƙasa."

75. Manyan gari waɗanda suka yi girman kai daga mutanensa, suka ce wa waɗanda suke raunana waɗanda suka yi imani daga cikinsu: “Yanzu kun san cewa Salihu Manzo ne daga wajen Ubangijinsa?” Sai suka ce; “Lalle mu dai mun yi imani da abin da aka aiko shi da shi.”

76. Waɗanda suka yi girman kai suka ce: “Lalle mu kuma mun kafirce wa abin da kuka yi imani da shi.”

77. Sai suka soke taguwar, suka kuma yi tsaurin kai game da umarnin Ubangijinsu, kuma suka ce: “Ya Salihu, ka zo mana da abin da kake mana alƙawarin zai same mu (na azaba) in ka kasance cikin manzanni.”

78. Sai wata girgizar ƙasa mai tsanani ta auka musu, sai suka wayi gari a gurfane kan gwiwoyinsu, (matattu) a cikin gidajensu.

79. Sai ya juya ya rabu da su, kuma ya ce: “Ya ku mutanena, lalle haƙiƙa na isar muku da saƙon Ubangijina, kuma na yi muku nasiha, sai dai ku ba kwa son masu nasiha.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba mu labarin cewa ya aika wa ƙabilar Samudawa ɗan’uwansu na jini Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Samudawa ƙabila ce daga cikin ƙabilun Larabawa da suka rayu a wani wuri da ake kiran sa *Al-Hijr*, yana nan a tsakanin Madina da ƙasar Sham. Kufan Samudawa har yanzu akwai shi, kuma ana kiran wurarensu da suna *‘Mada’inu Salih’*. Allah ya hallaka su saboda sun kafirce wa Annabinsa Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika wa Samudawa Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don ya kirawo su zuwa bauta wa Allah shi kaɗai da nisantar bautar wani abu ba shi ba, ya faɗa musu cewa, hujja mai ƙarfi daga Ubangijinsu ta zo musu tana tabbatar da kasancewarsa Manzo daga Allah. Wannan hujja kuwa ita ce taguwar da Allah ya ba shi don ta zama mu’ujiza mai nuna gaskiyar manzancinsa. Don haka ya gargaɗe su da cewa, su ƙyale ta ta ci arzikin Allah a bayan ƙasa, kada su kuskura su cutar da ita, za su gamu da azaba mai raɗaɗi.
Annabi Salihu ya neme su da su tuna ni’imar da Allah ya yi musu lokacin da ya maye gurbin mutanen Annabi Hudu da su bayan ya halaka su, ya zaunar da su a *Al-Hijr*, wani wuri tsakanin Madina da ƙasar Sham, suka riƙa yin manya-manyan gine-gine a wurare masu taushin ƙasa, kuma suna sassaƙa duwatsu suna mayar da su gidaje, don haka su tuna ni’imomin da Allah ya yi musu don su bauta masa shi kaɗai, su yi imani da Manzonsa Annabi Salihu, kada su yi ɓarna a bayan ƙasa.
Sai shugabanninsu masu girman kai suka ce wa raunanan muminai, wai yanzu su sun yarda Salihu Manzon Allah ne, ba ƙarya yake yi musu ba? Sai muminan suka amsa musu da cewa, su kam sun ba da gaskiya da shi. Sai shugabannin suka ce, su kam sun kafirce wa abin da muminai suka yi imani da shi, suka yi girman kai, suka ƙi bin umarnin Ubangijinsu, suka kashe wannan taguwar, suka ce da Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo musu da azabar da yake tsorata su da ita, idan har da gaske shi Manzon Allah ne. Sai kuwa azabar Allah ta auko musu, Allah ya aiko musu da wata tsawa mai ƙarfin gaske, mai girgiza ƙasa saboda tsananinta, sai duk suka zama gawarwaki a duddurƙushe kamar kututturen itacen dabino saboda tsawonsu da girman jikinsu.
Sai Annabi Salihu ya juya ya rabu da su yana mai zargin su a kan abin da ya same su, yana cewa, haƙiƙa shi kam ya isar musu da saƙon Allah, ya kuma yi musu nasiha, to amma kuma saboda ba sa son masu yi musu nasiha, nasiharsa ba ta yi musu amfani ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna mana cewa, rayuwar mutanen Annabi Luɗu rayuwa ce ta tumasanci da dabbanci, in ban da biyan buƙatar sha'awarsu babu abin da suka sa a gaba, don haka suke bin kowace irin ƙazantacciyar hanya don su biya wa kansu buƙatar sha'awarsu.

2. Wanda duk ya yarda da aikin wasu mutane, to tare da su za a haɗa shi, don haka ne Allah ya haɗa matar Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) tare da mutanensa suka halaka.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya jarrabar bawansa nagari, ko da kuwa shi annabi ne, da kangarewar matarsa ko ɗansa ko wani cikin danginsa.

4. Laifin matar Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne sanar da mutanen gari idan Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi baƙi. Amma ba ta taɓa yin zina ba. Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Babu matar wani Annabi da ta taɓa yin zina. [Ibn Jarir, *Tafsir* #18229].

5. Duk waɗanda aka same su suna aikata irin aikin mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), to hukuncinsu shi ne a jefe su, sun taɓa yin aure ko ba su taɓa yi ba.

Suratul A'araf (80-84)

وَلُوطًا إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ أَتَأْتُونَ ٱلْفَٰحِشَةَ مَا سَبَقَكُم بِهَا مِنْ أَحَدٍ مِّنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٨٠﴾ إِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلرِّجَالَ شَهْوَةً مِّن دُونِ ٱلنِّسَآءِۚ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ مُّسْرِفُونَ ﴿٨١﴾ وَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓاْ أَخْرِجُوهُم مِّن قَرْيَتِكُمْۖ إِنَّهُمْ أُنَاسٌ يَتَطَهَّرُونَ ﴿٨٢﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥٓ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ كَانَتْ مِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿٨٣﴾ وَأَمْطَرْنَا عَلَيْهِم مَّطَرًاۖ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٨٤﴾

80. Kuma ka tuna Luɗu lokacin da ya ce wa mutanensa: "Yanzu kwa riƙa aikata mummunan aikin da babu wani mahaluƙi a duniya da ya taɓa aikata irinsa gabaninku?

81. "Lalle ku kuna zaike wa maza don sha'awa maimakon mata. A'a, ku mutane ne maɓarnata."

82. Ba kuwa amsar da ta fito daga bakin mutanensa sai kawai suka ce: "Ku fitar da su daga garinku; lalle su mutane ne da suke nuna su masu tsarki ne."

83. Sai Muka tserar da shi da iyalansa, in ban da matarsa, ita ta kasance cikin waɗanda suka rage (a cikin azaba).

84. Sai Muka yi musu ruwan azaba; to duba ka ga yaya ƙarshen masu babban laifi ya kasance?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Shi dai Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ɗan ɗan'uwan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne, ya ba da gaskiya da baffansa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kuma ya yi hijira tare da shi daga ƙasar Iraƙi zuwa ƙasar Kan'ana, wato ƙasar Falasɗinu. Sai Allah ya ba shi manzanci tun lokacin rayuwar baffansa Annabi Ibrahimu

(Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya aike shi zuwa ga mutanen garin *Sadum;* sun kuma kasance mazauna wurin da a yanzu ake kira da Mataccen Teku ne *(Dead Sea)* da ke ƙasar Urdun *(Jordan)*. Waɗannan mutane sun shahara da wata mummunar ta'ada da ba a taɓa samun masu aikata irinta ba a gabaninsu. Wannan ta'ada kuwa ita ce zaike wa maza ta dubura. Kuma wani ƙarin abin takaicin suna gudanar da wannan ƙazantaccen laifi ne a gaban idon junansu. Bayan wannan kuma an san su da yawan aikata laifukan fashi da makami a kan hanyoyin matafiya, don haka sun hana matafiya da attajirai fatake sakat, suna tare su suna yi musu fashi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da Annabi Muhammadu (ﷺ) cewa, ya aiko musu Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don ya hana su aikata waɗannan miyagun laifuka, to amma sai suka ƙi sauraron sa, har ta kai ya yi musu addu'ar Allah ya hallaka su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ya karɓi addu'arsa ya aiko musu da ruwan azaba, ya kuma kifar da ƙasar, wato samanta ya koma ƙasa, ƙasanta ya koma sama, ya biyo su da ruwan duwatsu na wutar Jahannama. Allah kuma ya tserar da Annabi Luɗu da mutanensa in ban da matarsa wadda tana daga cikinsu waɗanda aka hallaka.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce wa Annabinsa Muhammadu (ﷺ), ya tuna Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da ya faɗa wa mutanensa cewa, yanzu sa riƙa aikata mummunan aikin da babu wani mahaluƙi da ya taɓa yin irinsa a gabaninsu? Ya faɗa musu cewa, suna zaike wa maza ta dubura domin buƙatar sha'awarsu, suna barin auren mata da Allah ya halatta musu, saboda kawai su mutane ne maɓarnatan gaske.
To amma da mutanensa suka tashi mayar masa da martani, sai kawai suka ce, a kori Annabi Luɗu shi da iyalansa daga wannan gari, ba don komai ba sai don sun nuna su mutane ne masu ƙyamar irin aikin mutanen wannan gari.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuɓutar da shi, shi da iyalansa, ban da matarsa kafira, ita an halakar da ita tare da waɗanda aka hallakar. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu ruwan duwatsu na taɓo mai tsananin ƙuna. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce wa, Annabi Muhammadu (ﷺ) ko mai ƙaratu ya duba ya ga yadda ƙarshen masu laifi ya zama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kamar sauran annabawan da suka gabace shi, ya fara da'awarsa ne da kira zuwa ga kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ibada da kauce wa haɗa shi da wani, domin a kan haka ne kowane irin aiki na ƙwarai zai ginu.

2. Al'ada ce ta annabawa idan sun fuskanci wani laifi da mutanensu suka fi raja'a a kansa fiye da sauran laifuka, to sukan fara wa'azinsu ta kansa ne bayan kiransu zuwa ga Tauhidi. Mutanen Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) laifin da suka fi aikatawa shi ne tauye mudu da sikeli, wannan ya sa ya fara wa'azinsa da kiran su zuwa ga cika mudu da sikeli da barin tauye wa mutane haƙƙoƙinsu. Don haka yana da kyau masu wa'azi su riƙa la'akari da haka, domin su kasance masu koyi da annabawa wajen da'awa.

3. Babu wani ci gaba da kowace al'umma za ta samu matuƙar ba ta bar saɓon Allah ba.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya umarni da wani abu ko ya hana wani abu sai wanda yake mai amfani ne ga bawa, ko mai cutarwa.

5. Riƙo da Tauhidi da kauce wa shirka muhimmin abu ne da yake ɗaukaka darajar mutum, ya gyara masa tunaninsa, ya raba shi da aiki da tatsuniyoyi ko ƙarairayi, ya 'yanta shi daga bautar wani ba Allah ba zuwa ga bautar Allah shi kaɗai.

6. Mumini yana samun sakayya ne a kan ayyukansa na ƙwarai saboda ya gina su a kan imani da Allah da ranar lahira, amma kafiri ba zai taba morar ladan wani aiki da ya yi na kirki ba a lahira saboda bai gina shi a kan tushen imani ba.

7. Wajibi ne mutum ya girmama hanyoyin da Allah ya shimfiɗa wa bayinsa don samun sakamako a wurinsa da yardarsa da rahamarsa a lahira.

8. Tuna ni'imomin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sa bawa ya yi wa Allah biyayya ya nisanci saɓon sa.

9. Tuna abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa maɓarnata na azaba yakan sa a guji saɓon sa da bin hanya irin tasu.

10. Hukuncin Allah ga bayinsa hukunci ne na adalci, duk waɗanda suka ga rayuwarsu a cikin ƙunci da takuruwa, to su sake duba halayensu, su koma kan tafarkin Allah, domin babu wata mafita sai wannan.

Suratul A'araf (85-87)

وَإِلَىٰ مَدۡيَنَ أَخَاهُمۡ شُعَيۡبٗاۚ قَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥۖ قَدۡ جَآءَتۡكُم بَيِّنَةٞ مِّن رَّبِّكُمۡۖ فَأَوۡفُواْ ٱلۡكَيۡلَ وَٱلۡمِيزَانَ وَلَا تَبۡخَسُواْ ٱلنَّاسَ أَشۡيَآءَهُمۡ وَلَا تُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ بَعۡدَ إِصۡلَٰحِهَاۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٨٥ وَلَا تَقۡعُدُواْ بِكُلِّ صِرَٰطٖ تُوعِدُونَ وَتَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ مَنۡ ءَامَنَ بِهِۦ وَتَبۡغُونَهَا عِوَجٗاۚ وَٱذۡكُرُوٓاْ إِذۡ كُنتُمۡ قَلِيلٗا فَكَثَّرَكُمۡۖ وَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ٨٦ وَإِن كَانَ طَآئِفَةٞ مِّنكُمۡ ءَامَنُواْ بِٱلَّذِيٓ أُرۡسِلۡتُ بِهِۦ وَطَآئِفَةٞ لَّمۡ يُؤۡمِنُواْ فَٱصۡبِرُواْ حَتَّىٰ يَحۡكُمَ ٱللَّهُ بَيۡنَنَاۚ وَهُوَ خَيۡرُ ٱلۡحَٰكِمِينَ ٨٧

85. Kuma (Mun) aika wa mutanen Madyana ɗan'uwansu Shu'aibu, ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi, haƙiƙa hujja ta zo muku daga Ubangijinku; don haka ku riƙa cika mudu, kuma ku (kiyaye) ma'auni, kuma kada ku tauye wa mutane abubuwansu, kuma kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan an gyara ta. Wannan shi ne mafi alheri a gare ku in kun kasance muminai.

86. "Kuma kada ku zauna a kan kowace hanya kuna tsoratar da (mutane), kuma kuna toshe hanyar Allah ga duk wanda ya yi imani da Shi, kuna kuma son ta zama karkatacciya. Kuma ku tuna (ni'imar Allah) lokacin da kuke 'yan kaɗan, sai Ya yawaita ku, kuma ku duba ku ga yaya ƙarshen maɓarnata ya kasance?

87. "Idan kuma an sami wata ƙungiya daga cikinku sun yi imani da abin da aka aiko ni da shi, wata ƙungiyar kuma ba su yi imani ba, to ku yi haƙuri har Allah Ya yi hukunci a tsakaninmu. Kuma Shi ne Fiyayyen masu hukunci."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba mu labarin mutanen Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Su dai Larabawa ne, ana kiran su da mutanen Madyana. *Madyana* wani gari ne da ke tsakanin Hijaz da tekun *Akaba* (*Gulf of Aqaba*) kusa da gaɓar Bahar Maliya *(Red Sea)*. A yanzu garin ya mutu babu sauran mutane a wurin.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don ya kirawo su zuwa ga bautar Allah shi kaɗai da barin bautar gumaka, ya kuma yi musu wa'azi a kan

muguwar al’adarsu ta tauye mudu ko sikeli lokacin awo, to amma ba su saurari kiransa ba, sun kangare masa, sai Allah ya hallaka su da wata girgizar ƙasa.
Farkon abin da Annabi Shu’aibu ya fara tun ƙarar mutanensa da shi shi ne ya sanar da su cewa, ya zo musu da wata bayyananniyar hujja daga Ubangijinsu wadda take nuna gaskiyar manzancinsa. Don haka su cika ma’auni da sikeli kada su tauye wa mutane haƙƙoƙinsu, kada kuma su riƙa yaɗa ɓarna a bayan ƙasa bayan gyaranta. Wannan maganar da ake faɗa musu idan sun karɓe ta sun yi aiki da ita, ya fi musu alheri idan su muminai ne. Ya kuma ja kunnensu a kan su daina zama a hanya suna tsorata mutane da kisa ko azabtarwa, suna kuma hana wanda ya yi imani ya bi Allah ya bi Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), suna son hanyar Allah ta zama a karkace, wato ta yi daidai da soye-soyen zukatansu. Sannan ya buƙaci su tuna lokacin da adadinsu ba shi da yawa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yawaita su. Su kuma tuna yadda ƙarshen maɓarnata ya zama.
Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya faɗa wa mutanensa cewa, idan wata ƙungiya daga cikinsu ta yi imani da abin da Allah ya aiko shi da shi na kaɗaita Allah da bauta da barin aikata ɓarna a bayan ƙasa, wata ƙungiyar kuma ba ta yi imani da hakan ba, to su yi haƙuri su saurara har lokacin da Allah zai yi hukunci a tsakaninsu, domin shi ne Fiyayyen masu hukunci, sai ya tseratar da muminai ya kuma halaka kafirai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Addinin mumini ya fi komai daraja a wurinsa, zai iya haƙuri ya rabu da garinsa ko ƙasarsa saboda ya tsira da addininsa.

2. Annabawa duka suna jin tsoron canzawar lamari daga kyakkyawa zuwa mummuna, don haka suke cikin fargaba da addu’ar Allah ya tsare musu imaninsu har zuwa mutuwa.

3. Azzalumai har kullum sukan yi wa mumini barazanar raba shi da wani abu na jin daɗin rayuwar duniya ko danne masa haƙƙinsa don ƙoƙarin banƙaro shi da ƙarfi zuwa ga ɓata.

4. Kasancewar mutumin kirki a kan wata mummunar hanya, sai daga baya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiryar da shi zuwa ga madaidaiciyar hanya, wannan ba ya zama aibu ko abin suka a gare shi, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya kama mutum da laifin da bai sani ba, har sai ya sanar da shi ya saɓa.

5. Alaƙa tsakanin mumini da danginsa kafirai tana yankewa ne matuƙar sun yi wa Allah taurin kai sun zaɓi kafirci a kan imani.

6. Bai halatta wani mumini ya yi baƙin ciki a kan waɗanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai saukar musu da azabarsa saboda kafircinsu ko zunubansu ba, domin ba su cancanci hakan ba, saboda ƙiyayyar da suka nuna wa Allah da Manzonsa.

7. Shiriya da ɓata duka suna hannun Allah, yana shiryar da wanda ya cancanci shiriya a cikin bayinsa, yana kuma ɓatar da wanda ya cancanci ɓata.

Suratul A’araf (88-93)

۞قَالَ ٱلۡمَلَأُ ٱلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُواْ مِن قَوۡمِهِۦ لَنُخۡرِجَنَّكَ يَٰشُعَيۡبُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَكَ مِن قَرۡيَتِنَآ أَوۡ لَتَعُودُنَّ فِي مِلَّتِنَاۚ قَالَ أَوَلَوۡ كُنَّا
كَٰرِهِينَ٨٨ قَدِ ٱفۡتَرَيۡنَا عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا إِنۡ عُدۡنَا فِي مِلَّتِكُم بَعۡدَ إِذۡ نَجَّىٰنَا ٱللَّهُ مِنۡهَاۚ وَمَا يَكُونُ لَنَآ أَن نَّعُودَ فِيهَآ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّنَاۚ

وَسِعَ رَبُّنَا كُلَّ شَيۡءٍ عِلۡمًاۚ عَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلۡنَاۚ رَبَّنَا ٱفۡتَحۡ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَ قَوۡمِنَا بِٱلۡحَقِّ وَأَنتَ خَيۡرُ ٱلۡفَٰتِحِينَ ٨٩ وَقَالَ ٱلۡمَلَأُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَوۡمِهِۦ لَئِنِ ٱتَّبَعۡتُمۡ شُعَيۡبًا إِنَّكُمۡ إِذٗا لَّخَٰسِرُونَ ٩٠ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلرَّجۡفَةُ فَأَصۡبَحُواْ فِي دَارِهِمۡ جَٰثِمِينَ ٩١ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ شُعَيۡبٗا كَأَن لَّمۡ يَغۡنَوۡاْ فِيهَاۚ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ شُعَيۡبٗا كَانُواْ هُمُ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٩٢ فَتَوَلَّىٰ عَنۡهُمۡ وَقَالَ يَٰقَوۡمِ لَقَدۡ أَبۡلَغۡتُكُمۡ رِسَٰلَٰتِ رَبِّي وَنَصَحۡتُ لَكُمۡۖ فَكَيۡفَ ءَاسَىٰ عَلَىٰ قَوۡمٖ كَٰفِرِينَ ٩٣

88. Sai manyan gari, waɗanda suka yi girman kai daga cikin mutanensa suka ce: “Lalle za mu fitar da kai, ya kai Shu’aibu, da waɗanda suka yi imani tare da kai, daga alƙaryarmu, ko kuma ku dawo cikin addininmu.” (Shu’aibu) ya ce: “Ko da muna ƙin (hakan)?”

89. “Haƙiƙa mun ƙirƙiri ƙarya, mun jingina wa Allah, in har muka komo cikin addininku, bayan kuwa Allah Ya tserar da mu daga gare shi. Kuma ba ma zai yiwu ba mu koma cikinsa sai dai idan Allah Ubangijinmu ne Ya ga dama. Kuma ilimin Ubangijinmu Ya yalwaci komai. Ga Allah kaɗai muka dogara. Ya Ubangijinmu, Ka yi hukunci tsakaninmu da mutanenmu da gaskiya, kuma Kai ne Fiyayyen masu hukunci.”

90. Sai manyan gari waɗanda suka kafirce daga cikin mutanensa, suka ce: “Wallahi idan kun bi Shu’aibu fa, lalle ku tabbas kuna cikin hasararru.”

91. Sai girgizar ƙasa ta kama su, suka wayi gari a gidajensu gurfane a kan gwiwoyinsu (matattu).

92. Waɗanda suka ƙaryata Shu’aibu, kai ka ce ba su taɓa zama a cikinsu (gidajensu) ba, lalle waɗanda suka ƙaryata Shu’aibu sun kasance su ne hasararru.

93. Sai ya juya ya bar su, kuma ya ce: “Ya ku mutanena, lalle haƙiƙa na isar muku da saƙonnin Ubangijina, na kuma yi muku nasiha; to saboda me zan ji takaici a kan mutane kafirai?”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin ƙissar Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa, yana bayyana lokacin da shugabanninsu masu girman kai suka yi masa barazanar korar sa tare da waɗanda suka yi imani da shi daga garinsu ko kuma in ba haka ba su koma tsohon addininsu da suka bari. Sai ya amsa musu da cewa, yanzu sai su iya mayar da su addininsu ko da kuwa ba sa son hakan? Ya ce, haƙiƙa shi da mutanensa sun yi wa Allah ƙarya idan har suka yarda suka koma addininsu na farko bayan Allah ya kuɓutar da su daga gare shi. Ya tabbatar musu da cewa, ba za ta yiwu su koma cikin wannan addini ba, sai dai idan Allah ne ya ga damar haka ta faru, domin iliminsa ya yalwaci komai. Ya ce sun dogara ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai a cikin duk al’amuransu. Sannan ya yi addu’a cewa, ya Ubangijinmu, ka yi hukunci a tsakaninmu da mutanenmu, ka ba mu nasara, domin kai ne Fiyayyen masu hukunci.
Sai shugabannin kafirai masu faɗa a ji suka faɗa wa waɗanda suke ƙarƙashinsu cewa, idan har suka yarda suka bi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), to lalle sun zama taɓaɓɓu hasararru.
To yayin da tura ta kai bango, mutanen Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ƙi yin imani da shi, sun kuma sha alwashin cutar da shi har da mabiyansa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da wata girgizar ƙasa mai tsanani ta same su, sai suka wayi gari matattu a duddurƙushe a cikin gidajensu. Allah ya halaka su kamar ba su taɓa zama a cikin gidajensu ba. Lalle waɗanda suka ƙaryata Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun tabbata su ne taɓaɓɓu, hasararru.

Daga nan Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya rabu da su yana cewa, ya dai isar musu da saƙon da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko shi da shi, ya kuma yi musu nasiha, don haka me zai sa shi ya yi baƙin ciki a kan abin da ya same su saboda kafircinsu?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ilimin sanin halayyar ɗan'adam ya tabbatar da cewa, wahalhalu da shiga cikin ƙunci da tasku sukan koyar da mutane tarbiyya su gyara musu halayyarsu. Yalwa da jin daɗi kuma sukan iya shagaltar da mumini har ya manta da rauninsa da buƙatuwarsa zuwa ga Ubangijinsa. Wahalhalu kuma sukan iya tuna wa kafiri ni'imomin Allah, ya fahimci ƙimarsu da darajarsu, sai ya zama mai godiya idan sun sake dawo masa, har ya tuba ya koma ga tafarkin gaskiya.

2. Saɓon Allah yakan iya bice albarkar addini da ta rayuwa.

3. Idan mutane suka yi imani kuma suka kiyaye dokokin Ubangijinsu, to shi kuma sai ya kwararo musu ni'imominsa marasa iyaka.

4. Bai dace da bawa ya saki jiki ba da cewa shi mai imani ne; wajibi ne ya zamanto a koyaushe yana jin tsoron kada Allah ya jarrabe shi ya raba shi da imaninsa.

5. Duk wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa hanyoyin shiriya, ya kuma ba shi labarin waɗanda ya hallaka su saboda zunubansu, kuma wannan bai sanya shi jin tsoron Allah ba, bai hana shi aikata zunubai ba, to Allah yana iya toshe masa zuciya ya hana masa sauraron gaskiya ya ɗauke ta.

6. A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci makarunsa shi kaɗai bai ambaci makarun bawansa ba. To amma a cikin *Suratul Anfal,* aya ta 30, Allah ya ambaci makarunsa da na bayinsa.

Makaru sifa ce da Allah ya siffanta kansa da ita a wani ƙayyadajjen wuri, bai halatta wani ya siffanta shi da ita ba sai a wurin da ya siffanta kansa da ita ko wurin da Manzonsa ya siffanta shi da ita. Kuma malamai sun haɗu a kan cewa, bai halatta a ciro sunan Allah daga cikinta ba, wato a ce yana daga sunayen Allah: Al-*Mãkiru*, wannan bai halatta ba.

7. Amince wa makarun Allah yana daga cikin manyan laifuka.

Suratul A'araf (94-100)

وَمَآ أَرۡسَلۡنَا فِي قَرۡيَةٖ مِّن نَّبِيٍّ إِلَّآ أَخَذۡنَآ أَهۡلَهَا بِٱلۡبَأۡسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ لَعَلَّهُمۡ يَضَّرَّعُونَ ٩٤ ثُمَّ بَدَّلۡنَا مَكَانَ ٱلسَّيِّئَةِ ٱلۡحَسَنَةَ حَتَّىٰ عَفَواْ وَّقَالُواْ قَدۡ مَسَّ ءَابَآءَنَا ٱلضَّرَّآءُ وَٱلسَّرَّآءُ فَأَخَذۡنَٰهُم بَغۡتَةٗ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٩٥ وَلَوۡ أَنَّ أَهۡلَ ٱلۡقُرَىٰٓ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَوۡاْ لَفَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَرَكَٰتٖ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ وَلَٰكِن كَذَّبُواْ فَأَخَذۡنَٰهُم بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٩٦ أَفَأَمِنَ أَهۡلُ ٱلۡقُرَىٰٓ أَن يَأۡتِيَهُم بَأۡسُنَا بَيَٰتٗا وَهُمۡ نَآئِمُونَ ٩٧ أَوَ أَمِنَ أَهۡلُ ٱلۡقُرَىٰٓ أَن يَأۡتِيَهُم بَأۡسُنَا ضُحٗى وَهُمۡ يَلۡعَبُونَ ٩٨ أَفَأَمِنُواْ مَكۡرَ ٱللَّهِۚ فَلَا يَأۡمَنُ مَكۡرَ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡقَوۡمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٩٩ أَوَ لَمۡ يَهۡدِ لِلَّذِينَ يَرِثُونَ ٱلۡأَرۡضَ مِنۢ بَعۡدِ أَهۡلِهَآ أَن لَّوۡ نَشَآءُ أَصَبۡنَٰهُم بِذُنُوبِهِمۡۚ وَنَطۡبَعُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ فَهُمۡ لَا يَسۡمَعُونَ ١٠٠

94. Kuma ba Mu taɓa aiko wani annabi cikin wata alƙarya ba, (mutanensa suka ƙaryata shi) sai Mun kama su da tsananin talauci da cututtuka, ko sa ƙasƙantar da kai.

95. Sannan sai Muka musanya mahallin tsanani da jin daɗi, har dai suka yawaita, suka ce: “Haƙiƙa da can cututtuka da kuma wadata sun samu iyayenmu.” Sai kawai Muka damƙe su (da azaba) ba zato ba tsammani alhalin ba sa jin (hakan zai faru).

96. Kuma in da a ce mutanen alƙaryu sun yi imani kuma sun tsare dokokin Allah, to lalle da Mun buɗe musu albarkatu daga sama da kuma ƙasa, sai dai sun ƙaryata, Mu kuwa sai Muka kama su da abin da suka kasance suna aikatawa.

97. Yanzu mutanen alƙaryu sun amince azabarmu ta zo musu cikin dare alhali suna bacci?

98. Ko kuma mutanen alƙaryun sun amince azabarmu ta zo musu da hantsi suna tsakiyar wasanni?

99. Yanzu sun amince da makarun Allah ne? To kuwa ba mai amince wa makarun Allah sai mutanen da suke asararru.

100. Ko kuwa bai bayyana ba ga waɗanda suke gaje ƙasa bayan gushewar mutanenta (na farko) cewa, idan da Mun ga dama da Mun kama su da zunubansu. Kuma da Mun rufe zukatansu don haka ba za su iya ji ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙarin bayani ne game da ƙissoshin da suka gabata da dalilan da sukan jawo Allah ya hallakar da wata al’umma ko ya saukar musu da wata azaba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu wani garin da ya aiko musu da wani annabi kuma suka ƙaryata shi, sai ya kama su da azabar talauci da cututtuka, domin su ƙaskantar da kansu gare shi, su roƙe shi don ya yaye musu wannan musifar. To amma sai ya zamanto hakan bai amfane su ba, sai su ci gaba da shisshigi cikin zunubi da kangara, sai Allah ya yi musu talala ya canza musu da jin daɗi maimakon wahalar da suke ciki, ya ba su lafiya, ya yawaita musu arzikinsu, har sai sun yi yawa, dukiyarsu da ‘ya’yansu ma sun bunƙasa sun yi yawa, sun manta da duk wahalhalun da suka taɓa samun su a baya, har suna ba da labarin cewa, a da can cututtuka da wadata sun sami iyayensu. To suna cikin haka kwatsam ba zato ba tsammani sai Allah ya kama su da azabarsa, alhali kuwa ba sa jin hakan zai faru.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da dai mutanen alƙaryu za su yi imani su kiyaye dokokin Allah, su gode wa ni’imominsa, da ya buɗe musu hanyoyin samun albarka daga sama da kuma ƙasa, to amma ba su yi hakan ba, maimakon hakan sai suka ƙaryata gaskiyar da ta zo musu, sai ko Allah ya hallakar da su saboda kafirci da manyan laifuka da suka aikata. To bayan wannan abu da ya faru, shin mutanen alƙaryun nan sun amince ne azabar Allah mai tsanani ta sauka a kansu cikin dare suna barci ko kuma ta zo musu da hantsi suna tsaka da wasa? Ko kuma sun amince wa makarun Allah ne? To babu mai amincewa da makarun Allah sai mutanen da suka tabbata taɓaɓɓu masu hasara. Shin ko kuwa waɗanda suka gaje ƙasa bayan halakar da mutanen cikinta na farko bai isa su gane cewa, Allah yana da iko idan ya ga dama ya halaka su saboda zunubansu, ya kuma rufe zukatansu, don haka ba za su ji gaskiya su karɓe ta ba?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya ƙi bin hanyar Allah, ya ƙi cika alƙawarinsa, to zai bi wasu hanyoyi ne na daban, ya fita daga biyayya ga Allah.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana lallashin zuciyar Manzonsa (ﷺ) da labaran annabawa da al’ummominsu da yadda Allah ya halaka su saboda kafirce wa annabawa da suka yi. Wannan yana nuna cewa, butulcewar mushirikai ga Manzon Allah (ﷺ) ba ya nuna gazawarsa wajen isar musu da saƙo ko yi

musu bayanin da za su fahimta; haka ya faru ne saboda Allah ya toshe zukatan yawancinsu ne, don haka suka kasa fahimtar gaskiya.

3. Duk wani manzo da Allah ya taɓa aikowa, to ya ba shi mu'ujizoji masu tabbatar da gaskiyar manzancinsa.

Suratul A'araf (101-103)

تِلْكَ ٱلْقُرَىٰ نَقُصُّ عَلَيْكَ مِنْ أَنۢبَآئِهَا ۚ وَلَقَدْ جَآءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَمَا كَانُوا۟ لِيُؤْمِنُوا۟ بِمَا كَذَّبُوا۟ مِن قَبْلُ ۚ كَذَٰلِكَ يَطْبَعُ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿١٠١﴾ وَمَا وَجَدْنَا لِأَكْثَرِهِم مِّنْ عَهْدٍ ۖ وَإِن وَجَدْنَآ أَكْثَرَهُمْ لَفَٰسِقِينَ ﴿١٠٢﴾ ثُمَّ بَعَثْنَا مِنۢ بَعْدِهِم مُّوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦ فَظَلَمُوا۟ بِهَا ۖ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿١٠٣﴾

101. Waɗancan alƙaryun Muna ba ka labarinsu ne. Kuma lalle haƙiƙa manzanninsu sun zo musu da hujjoji bayyananu, amma ba su kasance masu yin imani ba, saboda ƙaryatawar da suka yi a da. Kamar haka ne Allah Yake rufe zukatan kafirai.

102. Kuma yawancinsu ba Mu same su da riƙe wani alƙawari ba; haƙiƙa kuma Mun samu yawancinsu fasiƙai ne.

103. Sannan sai Muka aika Musa a bayansu da ayoyinmu, zuwa Fir'auna da manyan mutanensa, sai suka zalunci (kansu) da su; to duba ka ga, yaya ƙarshen maɓarnata ya kasance?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, waɗancan garuruwa da ƙissoshinsu suka gabata, yana ba shi labaransu ne don ya zama lallashi gare shi shi da muminai, ya kuma zama lallashi da kuma wa'azi ga masu wa'azantuwa, kuma su zama tsawatarwa da tsoratarwa ga kafirai. Manzanni sun zo wa mutanen waɗannan alƙaryu da hujjoji bayyanannu masu nuna gaskiyar manzancinsu, to amma sai suka ƙi yin imani, saboda sun ƙaryata gaskiya a lokacin da ta fara zuwa gare su. To kamar haka ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake doƒe zukatan kafirai, don haka har abada ba za su yi imani ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, bai samu yawancin al'ummomin da suka gabata suna cika alƙawarin da suka ɗauka ba; yawancinsu fasiƙai ne marasa tsoron Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, bayan wucewar waɗancan annabawa da ya ambaci ƙissoshinsu a baya, ya kuma aiko da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya ba shi mu'ujizoji da dalilai waɗanda suke tabbatar da gaskiyarsa, ya aika shi zuwa ga Fir'auna da manyan mutanensa, to amma sai girman kai ya sa suka kafirce wa ayoyin Allah, suka faɗa cikin zalunci a sanadiyyar haka. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya duba ya ga yadda ƙarshen maɓarnata ya zama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Al'adar annabawa ba su ne suke fara bayyana mu'ujizarsu ba, har sai an ƙalubalance su sai Allah ya bayyana ta don kiyaye martabar annabci kada a yi saurin ƙaryata su.

2. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zabi ya ambata wa Fir'auna siffar Allah ta *Rububiyyarsa* ga dukkan talikai, domin ya rushe da'awar Fir'auna ta cewa, shi ne ubangiji mafi ɗaukaka, kuma ya fito da siffar Allah ta kasancewarsa shi ne mahalicci kuma mai rainon halittunsa, ya tarbiyyance

su, don haka bai bar su sasakai ba sai da ya aiko musu da manzanni domin su nuna musu hanyar shiriya. Shi ne wanda babu mai ikon yin da'awar manzanci bisa ƙarya, face sai ya fallasa shi ya nuna wa jama'a ƙaryarsa a fili.

3. Neman a gayyato matsafa daga gari-gari yana nuna a wannan zamani matsafa sun yawaita a garuruwa kuma an ba tsafi muhimmanci.

4. Mu'ujizar kowane annabi tana dacewa ne da zamaninsa.

Suratul A'araf (104-112)

وَقَالَ مُوسَىٰ يَٰفِرۡعَوۡنُ إِنِّي رَسُولٞ مِّن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٠٤ حَقِيقٌ عَلَىٰٓ أَن لَّآ أَقُولَ عَلَى ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡحَقَّۚ قَدۡ جِئۡتُكُم بِبَيِّنَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ فَأَرۡسِلۡ مَعِيَ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ١٠٥ قَالَ إِن كُنتَ جِئۡتَ بِـَٔايَةٖ فَأۡتِ بِهَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ١٠٦ فَأَلۡقَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِيَ ثُعۡبَانٞ مُّبِينٞ ١٠٧ وَنَزَعَ يَدَهُۥ فَإِذَا هِيَ بَيۡضَآءُ لِلنَّٰظِرِينَ ١٠٨ قَالَ ٱلۡمَلَأُ مِن قَوۡمِ فِرۡعَوۡنَ إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٌ عَلِيمٞ ١٠٩ يُرِيدُ أَن يُخۡرِجَكُم مِّنۡ أَرۡضِكُمۡۖ فَمَاذَا تَأۡمُرُونَ ١١٠ قَالُوٓاْ أَرۡجِهۡ وَأَخَاهُ وَأَرۡسِلۡ فِي ٱلۡمَدَآئِنِ حَٰشِرِينَ ١١١ يَأۡتُوكَ بِكُلِّ سَحَّارٍ عَلِيمٖ ١١٢

104. Kuma Musa ya ce: "Ya kai Fir'auna, lalle ni Manzo ne daga Ubangijin talikai.

105. "Wajibi ne a kaina cewa ba zan faɗi wata magana game da Allah ba sai ta gaskiya. Haƙiƙa na zo muku da hujja bayyananniya daga Ubangijinku, don haka ka sakar min Banu Isra'ila."

106. Sai ya ce: "Idan har kana da wata alama, to ka zo da ita, idan har kana cikin masu gaskiya."

107. Sai ya jefar da sandarsa, sai ga shi ta zama wani irin ƙaton kumurci a fili.

108. Kuma ya zaro hannunsa, sai ga shi fari ƙal ga masu kallo.

109. Sai manyan gari daga cikin mutanen Fir'auna suka ce: "Lalle wannan tabbas mai sihiri ne, masani.

110. "Yana nufi ne ya fitar da ku daga ƙasarku, don haka me kuke yin umarni (da a yi)?"

111. Sai suka ce: "Ka dakatar da shi da ɗan'uwansa, ka kuma tura masu yin gangami cikin birane.

112. "Za su zo maka da duk wani ƙwararren matsafi."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana ƙissar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne da Fir'auna da mutanensa. Lokacin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga wajen Fir'auna ya sanar da shi cewa shi Manzon Allah ne zuwa gare shi, kuma Allah shi ne Ubangijin kowa, mahaliccin kowa da komai, kuma wajibi ne a kansa ba zai faɗi wata magana ya jingina ta ga Allah ba, sai gaskiya, kuma ya zo masa da hujja bayyananniya daga Ubangijinsa, saboda haka lalle ya sakar masa Banu Isra'ila waɗanda ya kama ya tsare su yana gallaza musu azaba ba bisa wani haƙƙi ba. Sai Fir'auna ya ce masa, idan har da gaske ne ya zo da wata hujja, to ya bayyana ta kowa ya gan ta. Sai Annabi Musa ya jefar da sandarsa, sai ga shi ta zama wani ƙaton kumurci kowa yana ganin sa, ya kuma fito da hannunsa daga rigarsa, sai ga shi fari ƙal kowa yana kallo.

To daga nan sai manyan mutane masu faɗa a ji daga cikin mutanen Fir’auna suka ce, lalle babu shakka Musa gogaggen matsafi ne wanda ya ƙware cikin sha’anin tsafi, kuma sun gane cewa so yake ya fitar da su daga ƙasarsu da wannan sihiri nasa, don haka me suke ganin ya kamata a yi masa? Sai manyan mutanen na Fir’auna suka ba shi shawarar cewa kamata ya yi, ya dakatar da Musa da ɗan’uwansa Haruna, ya tura gari-gari a yi masa gangami na manyan matsafa domin su tinkari Musa da tsafinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sihiri ba ya iya canza haƙikanin abu zuwa wani abin daban, sai dai ya zama rufa-ido kawai. Domin da matsafi yana iya juya wani abu zuwa wani abu da gaske, to da waɗannan matsafan ba za su nemi a biya su wani lada na zinare ko azurfa ba, da sai su arzuta kansu ta hanyar canza ƙasa ta zama zinare, da kuwa sai su iya juye mulkin Fir’auna ya koma nasu, su mayar da kawunansu sarakunan duniya.

2. Neman da Fir’auna ya yi matsafa su zo su taimaka masa don ya yi nasara ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wannan yana nuna wa kowa cewa Fir’auna ba Allah ne ba, shi bawa ne gajiyayye mai rauni, har yana neman wasu su taimaka masa a kan abin da ya fi ƙarfinsa shi kuma ya biya su.

3. Babu laifi a fara sauraron ƙiren marar gaskiya sannan daga baya a rushe ta da dalilai masu ƙarfi.

4. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yarda matsafa su fara nuna abin da suke taƙama da shi na tsafi domin yana da tabbacin cewa duk abin da za su zo da shi ƙarya ne, kuma ba za su taɓa cin nasara ba a kan gaskiyar da ya sakankance cewa daga Allah take.

Suratul A’araf (113-116)

وَجَآءَ ٱلسَّحَرَةُ فِرۡعَوۡنَ قَالُوٓاْ إِنَّ لَنَا لَأَجۡرًا إِن كُنَّا نَحۡنُ ٱلۡغَٰلِبِينَ ١١٣ قَالَ نَعَمۡ وَإِنَّكُمۡ لَمِنَ ٱلۡمُقَرَّبِينَ ١١٤ قَالُواْ يَٰمُوسَىٰٓ إِمَّآ أَن تُلۡقِيَ وَإِمَّآ أَن نَّكُونَ نَحۡنُ ٱلۡمُلۡقِينَ ١١٥ قَالَ أَلۡقُواْۖ فَلَمَّآ أَلۡقَوۡاْ سَحَرُوٓاْ أَعۡيُنَ ٱلنَّاسِ وَٱسۡتَرۡهَبُوهُمۡ وَجَآءُو بِسِحۡرٍ عَظِيمٖ ١١٦

113. Matsafan kuwa suka zo wa Fir’auna suka ce: “Shin tabbas muna da wani lada idan muka kasance masu rinjaye?”

114. Ya ce, “E, kuma ma tabbas kuna cikin makusanta.”

115. Sai suka ce: “Ya kai Musa, ko dai ka (fara) jefawa, ko kuwa mu mu kasance mu ne masu (fara) jefawa.”

116. Ya ce: “Ku jefa”. To yayin da suka jefa (sandunansu) sai suka sihirce idon mutane, kuma suka gigita su, suka zo da wani tsafi babba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin abin da ya faru bayan an gayyato ƙwararrun matsafa daga gari-gari sun iso fadar Fir’auna ta Masar. Da suka iso sai suka nemi tabbacin ko zai biya su idan har su suka yi rinjaye a kan Musa? Fir’auna ya ce tabbas, ba ma lada kaɗai zai ba su ba; zai mayar da su makusantansa a fada.
Sai matsafa suka tambayi Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, shi ne zai fara jefa sandarsa ko kuma su ne za su fara jefa nasu? Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya

umarce su da su fara jefa sandunansu. To suna jefawa kuwa sai kawai suka sihirce idanun mutane, suka jefa musu tsoro, suka nuna sihiri mai girma.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abin da ya faru ga sandar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wata mu'ujiza ce da ta fi ƙarfin aikin mutum, domin babu wanda ya isa ya juyar da wani abu daga jinsinsa zuwa wani jinsin daban, kamar sanda ta juye ta zama dabba mai rai mai motsi da kanta, tana haɗiye sanduna da igiyoyi sai dai Allah. Lalle wannan abu ne da yake tabbatar da akwai Allah mahalicci mai yin abin da ya ga dama kuma yake tabbatar da gaskiyar manzancin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
2. Matsafa sun ɗimauce da ganin abin da ya fito daga hannun Annabi Musa, don haka ba su san sa'adda suka faɗi suka yi sujjada ba, saboda ƙarfin dalilin da suka gani.

3. Matsafa sun yi amfani da iliminsu na tsafi saboda sun iya bambancewa tsakanin tsafinsu da mu'ujizar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Da a ce ba su da wani ilimi da ya danganci tsafi, to da sai su ɗauka cewa, shi ma Annabi Musa abin da ya zo da shi tsafi ne, sai dai kawai ya fi nasu ne.

4. Fir'auna ya ji tsoron kada imanin matsafa da Annabi Musa ya zama hujja a wajen mutanensa, sai nan take ya jefa su cikin ruɗani iri biyu: Na farko ya ce, haɗa baki suka yi suka ƙulla makirci, babu wata gaskiya da suka gani; na biyu ya nuna cewa sun yi haka ne don su ma su sami mulki irin nasa.

5. Duk abin da ya tabbata gaskiya ne daga Allah da Manzonsa, to yarda da shi da aiki da shi ba ya buƙatar sai wani ya ba da izini a kai. Don haka masu cewa sai sun yi wa Musulmi izinin yin salati ga Annabi (ﷺ) ko istigfari ko hailala, wannan ba Musulunci ne ba.

6. Marasa gaskiya idan sun kasa samun hujja ko an rinjaye su da ƙaƙƙarfan dalili, to sai su koma hanyar barazana ta ɗaukar mataki na cutar da mai gaskiya da nuna masa fin ƙarfi.

7. Idan imani ya zauna daram a zuciya, to mutum yakan daina jin tsoron uƙuba ta duniya, yakan yi tunanin uƙubar lahira ne, domin uƙubar duniya tana da iyaka, kuma mai sauƙi ce idan an gwada da ta lahira, kuma ladan imaninsa da zai samu a lahira ya fi jin daɗin da zai samu na duniya komai yawansa.

8. Musulunci shi ne addinin Allah a kowane wuri, kuma a kowane zamani.

Suratul A'araf (117-126)

*وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنۡ أَلۡقِ عَصَاكَۖ فَإِذَا هِيَ تَلۡقَفُ مَا يَأۡفِكُونَ ١١٧ فَوَقَعَ ٱلۡحَقُّ وَبَطَلَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١١٨ فَغُلِبُواْ هُنَالِكَ وَٱنقَلَبُواْ
صَٰغِرِينَ ١١٩ وَأُلۡقِيَ ٱلسَّحَرَةُ سَٰجِدِينَ ١٢٠ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٢١ رَبِّ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ١٢٢ قَالَ فِرۡعَوۡنُ ءَامَنتُم بِهِۦ قَبۡلَ أَنۡ ءَاذَنَ لَكُمۡۖ
إِنَّ هَٰذَا لَمَكۡرٞ مَّكَرۡتُمُوهُ فِي ٱلۡمَدِينَةِ لِتُخۡرِجُواْ مِنۡهَآ أَهۡلَهَاۖ فَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ١٢٣ لَأُقَطِّعَنَّ أَيۡدِيَكُمۡ وَأَرۡجُلَكُم مِّنۡ خِلَٰفٖ ثُمَّ لَأُصَلِّبَنَّكُمۡ
أَجۡمَعِينَ ١٢٤ قَالُوٓاْ إِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا مُنقَلِبُونَ ١٢٥ وَمَا تَنقِمُ مِنَّآ إِلَّآ أَنۡ ءَامَنَّا بِـَٔايَٰتِ رَبِّنَا لَمَّا جَآءَتۡنَاۚ رَبَّنَآ أَفۡرِغۡ عَلَيۡنَا صَبۡرٗا وَتَوَفَّنَا مُسۡلِمِينَ ١٢٦

117. Muka kuma yi wahayi ga Musa cewa: "Jefa sandarka." Sai ga shi nan take tana haɗiye abin da suke ƙagowa.

118. Sai gaskiya ta tabbata, abin da kuma suka kasance suna aikatawa sai ya lalace.

119. Sai aka rinjaye su a nan, suka kuma juya a ƙaskance.

120. Matsafa kuwa suka faɗi suna masu sujjada.

121. Suka ce: “Mun yi imani da Ubangijin talikai.

122. “Ubangijin Musa da Haruna.”

123. Sai Fir’auna ya ce: “Yanzu kun yi imani da shi tun kafin in yi muku izini? Lalle wannan tabbas wani makirci ne da kuka ƙulla shi a nan cikin garin, don ku fitar da mutanensa daga cikinsa; to da sannu za ku sani.

124. “Lalle zan yanyanke hannayenku da ƙafafuwanku a tarnaƙe, sannan kuma gaba ɗaya zan gicciye ku.”

125. Sai suka ce: “Mu kam lalle masu komawa ne ga Ubangijinmu.”

126. “Kuma ba don komai za ka azabtar da mu ba sai don kawai mun yi imani da ayoyin Ubangijinmu yayin da suka zo mana. Ya Ubangijinmu, Ka zubo mana haƙuri, kuma Ka karɓi rayukanmu muna Musulmi.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da hikaito mana abin da ya faru tsakanin Annabi Musa da matsafa bayan ya umarce su da su fara jefa sandunansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wahayi a lokacin ya jefa sandarsa bayan matsafa sun jefa sandunansu da igiyoyinsu, sai ga sandar tasa ta zama ƙaton kumurci tana ta haɗiye sanduna da igiyoyin matsafa waɗanda suka yi wa mutane rufa-ido har suna ganin su kamar wasu macizai ne na gaske. To a daidai lokacin ne gaskiya ta bayyana, tsafe-tsafensu duka suka lalace, aka kayar da su har da Fir’auna shi da fadawansa, suka zama ƙaskantattu wulaƙantattu. Matsafa kuma da suka ga girman Kudurar Ubangiji, gaskiya kuma ta bayyana, sai duk suka faɗi suka yi wa Allah sujjada, suka ce: “Mun ba da gaskiya da Ubangijin talikai, Ubangijin Musa da Haruna”. Daga nan fa sai hankalin Fir’auna ya tashi, ya dinga yi wa matsafa faɗa, yana cewa, yaya za su ba da gaskiya da Musa ba tare da ya yi musu izini ba? Sai ya fara tuhumar matsafan da cewa, da ma sun ƙulla wani makirci ne tare da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a cikin gari kafin su iso wurinsa, don su kori Kibɗawa daga gari su maye gurbinsu da Banu-Isra’ila. Don haka ya tabbatar musu cewa, sai sun ɗanɗana kuɗarsu. Zai yanke hannayen matsafan da ƙafafuwansu a tarnaƙe, watau hannun dama da ƙafar hagu, sannan kuma ya gicciye su gaba ɗaya. To sai waɗannan matsafan da suka yi imani suka ce, lalle su kam zuwa ga Ubangijinsu za su koma, kuma ba wani abu da ya sa Fir’auna yake jin haushinsu sai don kawai sun yi imani da ayoyin Ubangijinsu da suka zo musu ta hannun Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sannan suka roƙi Allah ya ƙara musu haƙuri, kuma ya karɓi ransu suna Musulmi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kamar yadda Bahaushe yake cewa, ba a mugun sarki sai mugun bafade. Manyan fadawan Fir’auna ne suke zuga shi a kan ya gaggauta ɗaukan mataki a kan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mabiyansa, ya yi maza-maza ya kawo ƙarshen lamarinsu, ba tare da la’akari da gaskiyar da suka gani ɓaro-baro ba.

2. Har kullum marasa gaskiya sukan tuhumi mai yin kira zuwa ga gaskiya da cewa, yana yaɗa ɓarna ne a bainar jama'a, don haka sun ɗauka faɗa da shi faɗa ne da maɓarnata.

3. Tun kafin haihuwar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Fir'auna yake ta karkashe 'ya'yan Banu Isra'ila maza, yana barin mata ba tare da bambancewa tsakanin waɗanda suka bi shi da waɗanda ba su bi shi ba. To amma yanzu da alama zai mayar da hankalinsa ne a kan kashe 'ya'yan muminan Banu Isra'ila su kaɗai, ban da 'ya'yan waɗanda ba su ba da gaskiya da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba.

4. Yana daga cikin mummunan halin Banu Isra'ila rashin godiyar Allah da ƙarancin haƙuri. A nan ma abin da ya faru ke nan, domin sun camfa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), suna ganin zuwansa bai amfane su da komai ba; ga shi Fir'auna ya ci gaba da cutar da su kamar yadda ya yi musu a baya.

5. Babban abin da duk wani mumini zai yi taƙama da shi, ya fake a wurinsa, shi ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nusar da Banu Isra'ila da su nemi taimako a wurin Allah, shi ne zai yi musu maganin duk abin da ya fi ƙarfinsu.

6. Abubuwa biyu su ne suke haifar da wasu abubuwa biyu: Neman taimakon Allah shi yake haifar da Allah ya gadar da ƙasa ga wanda ya ga dama; sannan haƙuri shi ne yake gadar da kyakkyawan ƙarshe.

7. Bayani a kan duk wanda ya ji tsoron Allah, ya kiyaye dokokinsa, to Allah zai taimake shi duniya da lahira.

Suratul A'araf (127-129)

وَقَالَ ٱلۡمَلَأُ مِن قَوۡمِ فِرۡعَوۡنَ أَتَذَرُ مُوسَىٰ وَقَوۡمَهُۥ لِيُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَيَذَرَكَ وَءَالِهَتَكَۚ قَالَ سَنُقَتِّلُ أَبۡنَآءَهُمۡ وَنَسۡتَحۡيِۦ نِسَآءَهُمۡ وَإِنَّا فَوۡقَهُمۡ قَٰهِرُونَ ١٢٧ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوۡمِهِ ٱسۡتَعِينُواْ بِٱللَّهِ وَٱصۡبِرُوٓاْۖ إِنَّ ٱلۡأَرۡضَ لِلَّهِ يُورِثُهَا مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۖ وَٱلۡعَٰقِبَةُ لِلۡمُتَّقِينَ ١٢٨ قَالُوٓاْ أُوذِينَا مِن قَبۡلِ أَن تَأۡتِيَنَا وَمِنۢ بَعۡدِ مَا جِئۡتَنَاۚ قَالَ عَسَىٰ رَبُّكُمۡ أَن يُهۡلِكَ عَدُوَّكُمۡ وَيَسۡتَخۡلِفَكُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرَ كَيۡفَ تَعۡمَلُونَ ١٢٩

127. Sai manyan gari cikin mutanen Fir'auna suka ce: "Yanzu za ka ƙyale Musa da mutanensa, don su yi ɓarna a bayan ƙasa, kuma ya watsar da kai da abubuwan bautarka?" Sai ya ce: "Lalle za mu karkashe 'ya'yansu maza, mu ƙyale 'ya'yansu mata da rai, kuma lalle mu masu rinjaye ne a kansu."

128. Sai Musa ya ce da mutanensa: "Ku nemi taimakon Allah, kuma ku yi haƙuri; lalle ƙasa mulkin Allah ce, Yana gadar da ita ga wanda Ya ga dama daga cikin bayinsa; kuma kyakkyawan ƙarshe yana tabbata ne ga masu taƙawa."

129. Sai suka ce: "An cutar da mu tun kafin ka zo mana, da kuma bayan ka zo mana." Sai ya ce: "Ta yiwu Ubangijinku Ya halakar da abokan gabarku, kuma Ya mayar da ku halifofi a bayan ƙasa, sai Ya ga kuma, me za ku aikata?"

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin abin da ya faru bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi nasara a kan matsafan Fir'auna, har sun yi imani da Allah Ubangijin talikai baki ɗaya.

Sai manyan masu faɗa a ji daga mutanen Fir’auna suka ce masa, yanzu haka zai ƙyale Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka yi imani da shi daga Banu Isra’ila su ci gaba da ɓarna a bayan ƙasa, su yi watsi da shi da iyayen gijinsa? Sai Fir’auna ya amsa musu da cewa: Zai ɗauki matakin karkashe ‘ya’yansu maza, ya ƙyale matansu, kuma shi tabbas ya fi ƙarfinsu.
To da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ji wannan barazana ta Fir’auna, sai ya nemi mutanensa da su nemi taimakon Allah, kuma su yi haƙuri, domin ƙasa ta Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ce, shi yake gadar da ita ga wanda ya ga dama daga bayinsa, kuma kyakkyawan ƙarshe yana ga masu kiyaye dokokin Allah.
To amma su kuma Banu Isra’ila sai suka ce da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su fa Fir’auna da mutanensa sun daɗe suna cutar su kafin zuwansa, yanzu ma kuma ga shi bayan zuwansa a matsayin Manzo daga Allah sun ci gaba da cutar da su. Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya lallashe su, ya kwantar musu da hankali, ya bayyana musu cewa, yana sa ran cewa Allah zai halaka maƙiyansu, Fir’auna da jama’arsa, su kuma ya sanya su masu maye gurbinsu a bayan ƙasa, don ya ga yadda su kuma kamun ludayinsu zai kasance.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Al’adar Allah ce ya jarrabi wata al’umma da wata musiba domin su wa’azantu, kuma su tuna ni’imar da a da suke cikinta, domin tsanani yana jawo tsoron Allah da mayar da al’amari gare shi.

2. A cikin sanar da wannan al’umma irin azabar da ta samu mutanen Fir’auna, akwai faɗakarwa gare su da su riƙa kauce wa aikata abin da zai jawo musu fushin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), domin ƙwace ni’ima daga wanda yake cikinta wata alama ce mai nuna ya aikata wani abu da ya jawo Allah ya rabu da shi.

3. Camfi yana daga cikin munanan aƙidu na kafirai. Wajibi ne Musulmi su nisance shi, su dogara lamuransu ga Allah shi kaɗai, bai dace camfi ya riƙa sa musu fargaba ba, domin komai yana hannun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne yake yin yadda ya ga dama, babu mai iya canza masa nufinsa.

Suratul A’araf (130-133)

وَلَقَدۡ أَخَذۡنَآ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ بِٱلسِّنِينَ وَنَقۡصٖ مِّنَ ٱلثَّمَرَٰتِ لَعَلَّهُمۡ يَذَّكَّرُونَ ١٣٠ فَإِذَا جَآءَتۡهُمُ ٱلۡحَسَنَةُ قَالُواْ لَنَا هَٰذِهِۦۖ وَإِن تُصِبۡهُمۡ سَيِّئَةٞ يَطَّيَّرُواْ بِمُوسَىٰ وَمَن مَّعَهُۥٓۗ أَلَآ إِنَّمَا طَٰٓئِرُهُمۡ عِندَ ٱللَّهِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ١٣١ وَقَالُواْ مَهۡمَا تَأۡتِنَا بِهِۦ مِنۡ ءَايَةٖ لِّتَسۡحَرَنَا بِهَا فَمَا نَحۡنُ لَكَ بِمُؤۡمِنِينَ ١٣٢ فَأَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمُ ٱلطُّوفَانَ وَٱلۡجَرَادَ وَٱلۡقُمَّلَ وَٱلضَّفَادِعَ وَٱلدَّمَ ءَايَٰتٖ مُّفَصَّلَٰتٖ فَٱسۡتَكۡبَرُواْ وَكَانُواْ قَوۡمٗا مُّجۡرِمِينَ ١٣٣

130. Kuma lalle haƙiƙa Mun jarrabi iyalin gidan Fir’auna da shekaru na fari da kuma tawayar ‘ya’yan itace, ko sa yi tuntuntuni.

131. Amma yayin da daddaɗan abu ya zo musu, sai su ce: “Da ma wannan namu ne.” Idan kuma mummunan abu ya same su, sai su camfa Musa da waɗanda suke tare da shi. Ku saurara, kawai dai mummunan abin da ya same su daga wajen Allah yake, amma yawancinsu ba sa sanin (haka).

132. Kuma suka ce: “Kowace irin aya ka zo mana da ita, don ka sihirce mu da ita, to fa mu ba za mu yi imani da kai ba.”

133. Sai Muka aika musu da ambaliyar ruwa da fara da ƙwarƙwata da kwaɗi da jini, a matsayin ayoyi daki-daki, sai suka yi girman kai, kuma suka kasance mutane masu babban laifi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa, ya jarrabi mutanen Fir'auna da fari da ƙarancin kayan amfanin gona ko hakan zai zame musu wa'azi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, su mutanen Fir'auna sun kasance duk sa'adda aka samu yalwa da abinci mai yawa a ƙasar Masar sai su riƙa cewa, wannan nasu ne, wato iyayen gijinsu ne suka yi musu ƙaramci da kyauta domin sun cancanci hakan. Amma idan wata musiba ce ta same su, ta fari ko rashe-rashen lafiya ko rayuka, sai su riƙa camfe Annabi Musa da waɗanda suke tare da shi suna cewa, wai saboda addinin da suka zo da shi ne ya sa waɗannan musibu suke ta sauka, domin wai sun fusata allolinsu. Amma kuma a gaskiya duk wata musiba da za ta same su wani abu ne muƙaddari daga Allah, domin ya zamo uƙuba gare su saboda laifukansu; babu hannun Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a ciki, sai dai yawancinsu ba sa ganewa.
Saboda izgili ma cewa suka yi kowace irin aya Annabi Musa zai zo musu da ita don ya raba su da addininsu, to su fa ba za su yi imani da shi ba. To sai ko Allah ya aiko musu da musibu kala-kala, wannan bayan wannan, ya fara da ambaliyar ruwa da ya riƙa cinye musu gidajensu da gonakinsu; ya aiko musu da fari, amfanin gonakinsu duka ya lalace; ya aiko musu da ƙwarƙwata ta riƙa cutar da su, ta hana su sakat; ya aiko musu kwaɗi suka riƙa cika gidajensu da kwanukan abincinsu; ya aiko musu da jini wanda har ruwan shansu sai da ya koma jini. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da waɗannan bala'o'i ne don su zama ayoyi daki-daki masu nuna gaskiyar manzancin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), to amma duk da haka sai suka yi girman kai, suka kangare, suka kasance masu laifi, suka ci gaba da saɓon Allah da kafirce wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mumini mai ƙaratun Alƙur'ani ya yi tunani game da tasirin da imani ya yi wa Annabi Musa da Annabi Haruna yayin da suka fuskanci mafi zaluncin sarakuna a zamaninsu, wato Fir'auna, suka yi kiran sa a kan ya bar kafirci da zalunci da ta'addancin da yake yi, ya kuma sako Banu Isra'ila da ya kama ya ɗaure yana bautar da su, yana gana musu azaba. Suka gargaɗe shi, suka tsoratar da shi azabar Allah, ba su gushe ba suna ta bugawa da shi da hujjoji da bayyanannun ayoyi har Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su nasara a kansa, suka kuɓutar da mutanensu daga zaluncinsa. Don haka ya dace ƙwarai ga muminai bayan sun yi tunani a kan wannan, to su yi tunani a kan alƙwarin da Allah ya ɗaukar wa muminai ta hanyar manzanninsa cewa, idan har sun tsaya a kan bin umarnin Allah da kauce wa haninsa, na cewa zai ba su nasara, to kada ƙarfin wani azzalumi ya sa su yi sanyi wajen ƙwato haƙƙinsu; su sani cewa wanda ya taimaki masu gaskiya a da yayin da ba su fi mutum ɗaya ko biyu ba, to ba zai gagara ya taimake su ba a yau alhalin suna ɗaruruwan miliyoyi.

2. Duk mai haƙuri ƙarshensa zai ci nasara da ikon Allah.

3. Wani daga cikin magabata ya kafa hujja da wannan aya ta 137 a kan cewa, ba ya halatta a yi fito-na-fito da wani azzalumin mai mulki, sai dai a yi haƙuri da shi har lokacin da Allah zai rusa shi. [Ibn Aɗiyya, *Tafsir*, Juzu'i na 2, Shafi na 447].

وَلَمَّا وَقَعَ عَلَيۡهِمُ ٱلرِّجۡزُ قَالُواْ يَٰمُوسَى ٱدۡعُ لَنَا رَبَّكَ بِمَا عَهِدَ عِندَكَۖ لَئِن كَشَفۡتَ عَنَّا ٱلرِّجۡزَ لَنُؤۡمِنَنَّ لَكَ وَلَنُرۡسِلَنَّ مَعَكَ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ١٣٤ فَلَمَّا كَشَفۡنَا عَنۡهُمُ ٱلرِّجۡزَ إِلَىٰٓ أَجَلٍ هُم بَٰلِغُوهُ إِذَا هُمۡ يَنكُثُونَ ١٣٥ فَٱنتَقَمۡنَا مِنۡهُمۡ فَأَغۡرَقۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡيَمِّ بِأَنَّهُمۡ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَكَانُواْ عَنۡهَا غَٰفِلِينَ ١٣٦ وَأَوۡرَثۡنَا ٱلۡقَوۡمَ ٱلَّذِينَ كَانُواْ يُسۡتَضۡعَفُونَ مَشَٰرِقَ ٱلۡأَرۡضِ وَمَغَٰرِبَهَا ٱلَّتِي بَٰرَكۡنَا فِيهَاۖ وَتَمَّتۡ كَلِمَتُ رَبِّكَ ٱلۡحُسۡنَىٰ عَلَىٰ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ بِمَا صَبَرُواْۖ وَدَمَّرۡنَا مَا كَانَ يَصۡنَعُ فِرۡعَوۡنُ وَقَوۡمُهُۥ وَمَا كَانُواْ يَعۡرِشُونَ ١٣٧

134. Kuma yayin da azaba ta sauka a kansu, sai suka ce: “Ya kai Musa, ka roƙa mana Ubangijinka, saboda alƙawarin da Ya yi maka; lalle idan har ka yaye mana wannan azaba, to tabbas za mu yi imani da kai, kuma za mu sakar maka Banu Isra’ila.”

135. To yayin da Muka yaye musu wannan azaba zuwa wani lokacin da za su kai gare shi, sai ga shi suna warware alƙawarin da suka yi.

136. Sai Muka azabtar da su, Muka dulmiyar da su a cikin kogi saboda sun ƙaryata ayoyinmu, kuma sun kasance gafalallu game da su.

137. Mutanen kuma da ake nuna musu fin ƙarfi a da, Muka gadar musu gabashi da yammacin ƙasar da Muka yi wa albarka; kuma kalmar Ubangijinka kyakkyawa sai ta tabbata a kan Banu Isra’ila saboda haƙurin da suka yi; kuma Muka rushe abin da Fir’auna ya kasance yana yi shi da mutanensa, da abin da suka kasance suna ginawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da mu cewa, lokacin da azabar Allah ta sauka a kan Fir’auna da jama’arsa da dangogin annoba da suka riƙa gani iri-iri, sai suka nemi Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙa musu Allah da abin da Allah ya yi masa wasiyya ya roƙe shi da shi, don ya yaye musu matsalolinsu. Suka kuma yi masa alƙawari har da rantsuwa cewa, idan har ya yaye musu wannan azabar, to lalle za su yi imani da shi, kuma za su sakar masa Banu Isra’ila da Fir’auna yake tsare da su bisa zalunci. To amma lokacin da Allah ya yaye musu wannan azabar, ya kuma jinkirta musu har zuwa lokacin da ya aje domin halakar da su, sai ga shi sun warware alƙawarin da suka yi masa na za su yi imani, kuma za su sako Banu Isra’ila, sai Allah ya nutsar da su cikin kogi suka halaka, saboda sun ƙaryata ayoyinsa, kuma sun kasance gafalallu daga gare su.Kuma mutanen da ake wulaƙantarwa, ana bautar da su a da, wato Banu Isra’ila, sai Allah ya gadar musu da gabashi da yammacin ƙasar Sham wadda Allah ya yi mata albarka, ya cika musu alƙawarin da ya yi musu na halaka maƙiyansu ya ba su iko a bayan ƙasa, saboda haƙurin da suka yi, ya rushe duk wani abu da Fir’auna da mutanensa suka riƙa aikatawa da abin da suka yi ta ginawa na manyan gine-gine da dangogin abubuwan jin daɗi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daɗewar Banu-Isra’ila ƙarƙashin baƙin mulkin Fir’auna da mutanensa a Masar ya sanya su sun manta da wasiyyar kakansu Annabi Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) na su zama Musulmi masu bautar Allah shi kaɗai, kada su bauta wa kowa sai shi.

2. Alama ce da ke nuna dakushewar hankalin al’umma ta ga wani abu mai matuƙar muni amma ta zace shi mai kyau ne, har ma ta riƙa ƙoƙarin kawo shi cikin ‘ya’yanta, ta manta da kamalar da Allah ya yi mata.

3. Wajibi ne ga mai da’awa ya riƙa haƙuri a kan abin da zai gani ko ya ji daga waɗanda yake ƙoƙarin gyara musu halaye ko addini, na kakkaucewa da sakin kyakkyawar koyarwa da ƙoƙarin komawa ruwa a wasu lokuta.

4. Jahilci da wauta da ƙarancin hankali su ke jawo wa mutum ya saki Tauhidi, ya koma shirka.

5. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kausasa wa Banu Isra’ila amsa yayin da suka neme shi ya samar musu da wani abin bauta ba Allah ba, domin wannan muhalli ne na kausasawa.

6. Bautar wanin Allah aikin banza ne, kuma halaka ce ta duniya da lahira.

Suratul A’araf (138-141)

وَجَٰوَزۡنَا بِبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱلۡبَحۡرَ فَأَتَوۡاْ عَلَىٰ قَوۡمٖ يَعۡكُفُونَ عَلَىٰٓ أَصۡنَامٖ لَّهُمۡۚ قَالُواْ يَٰمُوسَى ٱجۡعَل لَّنَآ إِلَٰهٗا كَمَا لَهُمۡ ءَالِهَةٞۚ قَالَ إِنَّكُمۡ قَوۡمٞ تَجۡهَلُونَ ١٣٨ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ مُتَبَّرٞ مَّا هُمۡ فِيهِ وَبَٰطِلٞ مَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٣٩ قَالَ أَغَيۡرَ ٱللَّهِ أَبۡغِيكُمۡ إِلَٰهٗا وَهُوَ فَضَّلَكُمۡ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٤٠ وَإِذۡ أَنجَيۡنَٰكُم مِّنۡ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ يَسُومُونَكُمۡ سُوٓءَ ٱلۡعَذَابِ يُقَتِّلُونَ أَبۡنَآءَكُمۡ وَيَسۡتَحۡيُونَ نِسَآءَكُمۡۚ وَفِي ذَٰلِكُم بَلَآءٞ مِّن رَّبِّكُمۡ عَظِيمٞ ١٤١

138. Kuma sai Muka tsallakar da Banu Isra’ila kogi, sai suka tarar da waɗansu mutane da suka duƙufa a kan (bautar) gumakansu, suka ce: “Ya kai Musa, ka sa mana wani abin bauta, irin yadda waɗannan suke da abubuwan bauta.” Sai ya ce: “Lalle ku mutane ne da kuke da jahilci.

139. “Lalle waɗannan abin da suke cikinsa halaka ne, kuma abin da suke aikatawa ɓarna ce.”

140. Ya ce: “Shin yanzu wani wanda ba Allah ba zan nemo muku a matsayin abin bauta, alhali Shi ne Ya fifita ku a kan sauran talikai?”

141. Kuma ku tuna lokacin da Muka tserar da ku daga mutanen Fir’auna, (waɗanda) suke ɗanɗana muku mummunar azaba; suna karkashe ‘ya’yanku maza, kuma suna barin ‘ya’yanku mata da rai, kuma lalle a cikin wannan akwai wata jarraba babba daga Ubangijinku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, bayan ya halaka Fir’auna da jama’arsa, ya tserar da Banu-Isra’ila sun tsallake kogi, sai suka zo wucewa ta gaban wasu mutane mushirikai masu bautar gumaka ba Allah ba, sai suka nemi Annabi Musa su ma ya samar musu wani abin bauta ba Allah ba wanda za su riƙa bauta wa. Lokacin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ji wannan ɗanyar magana daga Banu-Isra’ila sai ya amsa musu da cewa, su dai mutane ne da har yanzu suke cikin jahilci, ba su san Allah ba. Waɗannan mutane abin da suke bauta wa ba Allah ba, halaka ce suke cikinta, kuma abin da suke yi ɓarna ne, aikin banza ne, ba zai amfane su da komai ba.

An karɓo daga Abu Waƙid Al-Laisi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da Manzon Allah (ﷺ) ya bar Hunainu, ya wuce ta gaban wata bishiya wadda ake kira da suna Zatu Anwaɗin, mushirikai sun rataye takubbansu a jikinta wai suna neman albarka a wajenta, sai wasu daga cikin Musulmin da ke tare da shi suka ce: “Ya Manzon Allah, mu ma a samar mana irin wannan bishiyar da za mu riƙa rataye makamanmu a jikinta kamar yadda waɗannan mutane suke yi.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Tsarki ya tabbata ga Allah, wannan ita ce irin maganar da mutanen Annabi Musa suka faɗa masa: ‘Ka sama mana abin bauta

mana kamar yadda su ma suke da abin bauta.’ Na rantse da wanda raina yake a hannunsa, lalle sai kun bi hanyar waɗanda suka gabace ku.” [Ahmad #21897, da Tirmizi #2180].

Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi mamakin Bani Isra’ila da har suka fara manta ni’imar da Allah ya yi musu, ta fifita su a kan sauran halittu na zamaninsu, to amma yanzu su ne kuma suke son a kawo musu wani abin bauta daban ba shi ba. Sai ya sake tuna musu kaɗan daga ni’imomin da Allah ya yi musu, watau kubutar da su daga hannun mutanen Fir’auna yayin da suke ɗanɗana musu azaba da wulaƙanci, suna kashe musu ‘ya’yansu maza suna barin matan domin su riƙa bautar da su a gidajensu, kuma suna cin mutuncinsu. Wannan wata babbar jarraba ce Allah ya yi wa Banu-Isra’ila a lokacin, bai kamata har su manta da ita ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawari da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) na dare talatin, sannan ya cike shi da dare goma ya zama arba’in. Ya yi haka ne domin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shirya wa zuwan lokacin wannan alƙawarin, su ma Banu-Isra’ila su fahimci saukar da Attaura wannan babban al’amari ne gare su, kuma don su yi ta ɗokin faruwar hakan.

2. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa Annabi Haruna wasiyya cikakkiya wadda ta ƙunshi bayanin yadda ake gudanar da mulkin al’umma. Ana so a ɗora harsashin tubalin gudanar da siyasar shugabanci a kan gyara, wato a tabbatar duk abin da al’umma za ta aikata yana tafiya bisa turbar gyara, wato ayyukansu su zamanto duk na alheri ne gare su da wasunsu. Duk wanda zai aikata aikin da shi kaɗai ne zai ga amfaninsa amma sauran mutane za su cutu daga wannan aiki nasa, to bai halatta ya aikata shi ba, domin ba daidai ne ba.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da yin abin da yake daidai ne, ya kuma hana aikata ɓarna, ya aiko da manzanni domin samar da maslahohi da inganta su da kawar da ɓarna da rage yawanta.

4. Kasancewar Musulmi mai yi wa ɗan’uwansa Musulmi nasiha ne, kuma nasiha haƙƙi ne na wajibi na Musulmi a kan ɗan’uwansa, wannan ya sa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa ɗan’uwansa Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) nasiha tare da cewa ya san shi ma Annabi ne da Allah ya aiko shi.

5. Jin daɗin maganar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi shi ne ya sanya shi ya roƙi Allah ya ba shi damar ganin sa ido-da-ido.

6. Yana daga cikin hujjojin cewa muminai za su ga Ubangijinsu ranar alƙiyama, bayyanar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi ga dutse wanda yake sandararren halitta ne, babu lada ko alhaki a kansa. To idan har haka za ta faru gare shi, me zai hana Allah ya bayyana kansa ga annabawa da manzanni da waliyyai a ranar lahira, gidan ƙaramci gare su? Allah ya nuna wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, dutse duk ƙarfinsa bai iya jure wa bayyanar Allah a kansa ba, to ta yaya shi ɗan’adam mai rauni zai iya jurewa?

*وَوَٰعَدۡنَا مُوسَىٰ ثَلَٰثِينَ لَيۡلَةٗ وَأَتۡمَمۡنَٰهَا بِعَشۡرٖ فَتَمَّ مِيقَٰتُ رَبِّهِۦٓ أَرۡبَعِينَ لَيۡلَةٗۚ وَقَالَ مُوسَىٰ لِأَخِيهِ هَٰرُونَ ٱخۡلُفۡنِي فِي قَوۡمِي وَأَصۡلِحۡ وَلَا تَتَّبِعۡ سَبِيلَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ١٤٢ وَلَمَّا جَآءَ مُوسَىٰ لِمِيقَٰتِنَا وَكَلَّمَهُۥ رَبُّهُۥ قَالَ رَبِّ أَرِنِيٓ أَنظُرۡ إِلَيۡكَۚ قَالَ لَن تَرَىٰنِي وَلَٰكِنِ ٱنظُرۡ إِلَى ٱلۡجَبَلِ فَإِنِ ٱسۡتَقَرَّ مَكَانَهُۥ فَسَوۡفَ تَرَىٰنِيۚ فَلَمَّا تَجَلَّىٰ رَبُّهُۥ لِلۡجَبَلِ جَعَلَهُۥ دَكّٗا وَخَرَّ مُوسَىٰ صَعِقٗاۚ فَلَمَّآ أَفَاقَ قَالَ سُبۡحَٰنَكَ تُبۡتُ إِلَيۡكَ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٤٣

142. Mun kuma yi wa Musa alƙawarin dare talatin, muka kuma cika su da goma, sai miƙatin Ubangijinsa ya cika darare arba’in cif-cif. Sai Musa ya ce da ɗan’uwansa Haruna: “Ka wakilce ni a cikin mutanena, kuma ka daidaita (tsakaninsu), kada kuma ka bi tafarkin maɓarnata.”

143. Lokacin Kuma da Musa ya zo wajen da muka yi alƙawari da shi, Ubangijinsa kuma Ya yi magana da shi, sai ya ce: “Ya Ubangijina, nuna mini kanka in gan Ka.” Sai ya ce: “Ba za ka iya gani Na ba, amma dubi dutsen nan, idan ya tabbata a bigirensa, to da sannu za ka gan Ni.” To lokacin da Ubangijinsa Ya bayyana (da haskensa) ga dutsen, sai Ya mayar da shi rugu-rugu, sai Musa ya faɗi sumamme. To yayin da ya farfaɗo, sai ya ce: “Tsarki ya tabbata gare Ka, na tuba zuwa gare Ka, kuma ni ne farkon muminai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa, ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) alƙawarin ganawa da shi bayan shuɗewar dare talatin yana sauraro, kuma ya cika masa da wa’adin dare goma, wanda ya cika dare arba’in yana bauta wa Allah a cikinsu. Bayan ya gama ne Allah ya gana da shi, ya yi magana da shi, ya kuma ba shi littafin Attaura.
Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai tafi wannan ganawar ba sai da ya umarci ɗan’uwansa Annabi Haruna da ya zauna madadinsa a cikin Banu-Isra’ila yana kula da su, yana yi musu gyara a inda duk ya ga ya dace, kada ya bi wata hanyar ɓata.
To lokacin ganawar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Ubanijinsa ya yi magana da shi ne kai-tsaye ba tare da wani a tsakaninsu ba, sai ya nemi alfarmar Ubangijinsa da ya ba shi damar ya gan shi a fili, sai ya faɗa masa cewa, ba zai yiwu ya gan shi a duniya ba, amma ya umarce shi da ya kalli wani dutse, idan ya tabbata a wurinsa, to zai iya ganin Allah. Yayin da Allah ya bayyana ga dutsen, sai ya dare ya yi rugu-rugu, Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuwa ya faɗi sumamme. To bayan ya farfaɗo ne sai ya tsarkake Allah, ya tuba zuwa gare shi, ya ce shi ne farkon muminai.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash’ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya tsaya cikinmu ya faɗa mana maganganu biyar. Ya ce: “Lalle Allah mai girma da buwaya ba ya barci, kuma bai dace ya yi barci ba; yana yin ƙasa da sikeli, kuma yana yin sama da shi; ana kai masa aikin dare kafin aikin rana, da aikin rana kafin na dare; shamakinsa haske ne – a wata ruwayar wuta ce – da a ce zai yaye shi, to da hasken fuskarsa ya ƙona ɗaukacin halittarsa da ganinsa yake zuwa gare ta.” [Muslim #179].

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Mutane za su suma a ranar alƙiyama; ni ne zan fara farfaɗowa, sai kawai in ga Musa tsaye yana riƙe da ƙafa ɗaya daga cikin ƙafafuwan Al’arshi, to ban sani ba; shin ya riga ni farfaɗowa ne, ko kuma an saka masa ne a madadin suman da ya yi a wurin dutsen Ɗuri.” [Bukhari #3398, da Muslim #2374].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya riƙe littafin Attaura da ƙarfi, kuma ya gode wa Allah bisa zaɓin da ya yi masa da kyautar ni'imomi da ya ba shi. Wannan ƙarantarwa ce da nusarwa game da yadda ya wajaba a mu'amalanci ni'imar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Manzanni su ne abin koyi ga mutane, don haka wajibi ne a kan mutane su gode wa Allah a kan kowace irin ni'ima da zai yi musu domin ya ƙara musu. Sannan yin hakan yana tsarkake zuciya, ya gyara ta, ya cire cutar butulci daga cikinta, ya ƙara ɗanƙon alaƙa tsakanin bawa da Ubangijinsa.

2. Wajibi ne muminai su riƙe littafin Allah da ƙarfin gaske, domin zartar da abin da ya zo da shi na shari'a da gyara da kafa al'umma ta gari. Masu kira zuwa ga Allah da malamai su ne ya fi zama wajibi a kansu su riƙe wannan littafi da kyau, domin su zama ababen koyi ga al'umma.

Suratul A'araf (144-145)

قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّي ٱصۡطَفَيۡتُكَ عَلَى ٱلنَّاسِ بِرِسَٰلَٰتِي وَبِكَلَٰمِي فَخُذۡ مَآ ءَاتَيۡتُكَ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ١٤٤ وَكَتَبۡنَا لَهُۥ فِي ٱلۡأَلۡوَاحِ مِن كُلِّ شَيۡءٖ مَّوۡعِظَةٗ وَتَفۡصِيلٗا لِّكُلِّ شَيۡءٖ فَخُذۡهَا بِقُوَّةٖ وَأۡمُرۡ قَوۡمَكَ يَأۡخُذُواْ بِأَحۡسَنِهَاۚ سَأُوْرِيكُمۡ دَارَ ٱلۡفَٰسِقِينَ ١٤٥ قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّي ٱصۡطَفَيۡتُكَ عَلَى ٱلنَّاسِ بِرِسَٰلَٰتِي وَبِكَلَٰمِي فَخُذۡ مَآ ءَاتَيۡتُكَ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ١٤٤ وَكَتَبۡنَا لَهُۥ فِي ٱلۡأَلۡوَاحِ مِن كُلِّ شَيۡءٖ مَّوۡعِظَةٗ وَتَفۡصِيلٗا لِّكُلِّ شَيۡءٖ فَخُذۡهَا بِقُوَّةٖ وَأۡمُرۡ قَوۡمَكَ يَأۡخُذُواْ بِأَحۡسَنِهَاۚ سَأُوْرِيكُمۡ دَارَ ٱلۡفَٰسِقِينَ ١٤٥

144. Ya ce: "Ya kai Musa, Lalle Ni na zaɓe ka a kan sauran mutane da saƙona da kuma zancena, don haka ka riƙe abin da na ba ka, kuma ka kasance cikin masu godiya."

145. Mun kuma rubuta masa komai a cikin allunan (Attaura) don wa'azi da bayani filla-filla na kowane irin abu, don haka ka riƙe su da kyau, kuma ka umarci mutanenka su yi riƙo da mafi kyawun abin da yake cikinsu. Da sannu zan nuna muku gidajen fasiƙai."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, ya zaɓe shi ya fifita shi a kan mutanen zamaninsa yayin da ya aiko shi da manzanci zuwa ga Banu-Isra'ila, kuma ya yi magana da shi ba tare da wani a tsakaninsu ba, ya kuma umarce shi ya riƙe littafin Attaura da ƙarfi, ya yi aiki da abin da yake cikinsa na shari'a, kuma ya zamanto cikin masu godiya ga Allah.
Ya kuma sanar da shi cewa, a cikin allunan Attaura ya rubuta masa duk wani abu da zai buƙata na addini da rayuwa don ya zamanto wa'azi gare shi da al'ummarsa Banu-Isra'ila, ya kuma zamo bayani filla-filla ga duk wani abu mai buƙatar ƙarin bayani. Ya umarce shi da ya riƙe abin da aka rubuta masa da ƙarfi, kuma ya umarci mutanensa su yi riƙo da mafi kyan abin da yake cikin Attaura. Allah kuma ya faɗa musu cewa, zai nuna musu gidan fasiƙai. Wasu malamai sun ce ana nufin wutar Jahannama, wato a lahira ke nan. Wasu kuma sun ce ana nufin ƙasar Baitil Maƙadisi, saboda mazauna cikinta a wannan lokaci mushirikai ne, masu bautar wanin Allah, don haka alƙawari ne Allah ya yi musu cewa, zai nuna musu wannan ƙasar. Yayin da wasu malamai suna ganin wannan gidan ana nufin ƙasar Masar da Baitil Maƙadisi ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin haɗarin girman kai ba da wani dalili ba.

2. Tataccen imani ba ya shiga zuciyar da take ɗauke da ƙazantar girman kai da hassada. Mai girman kai ba zai iya tsayawa ya yi tunani a kan duk wata gaskiya da ake faɗa masa ba, saboda yadda ji-ji da kai ya riga ya shiga zuciyarsa.

3. Mai girman kai ba zai dace da fahimtar Alƙur'ani ba.

Suratul A'araf (146-147)

سَأَصۡرِفُ عَنۡ ءَايَٰتِيَ ٱلَّذِينَ يَتَكَبَّرُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَإِن يَرَوۡاْ كُلَّ ءَايَةٖ لَّا يُؤۡمِنُواْ بِهَا وَإِن يَرَوۡاْ سَبِيلَ ٱلرُّشۡدِ لَا يَتَّخِذُوهُ سَبِيلٗا وَإِن يَرَوۡاْ سَبِيلَ ٱلۡغَيِّ يَتَّخِذُوهُ سَبِيلٗاۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَكَانُواْ عَنۡهَا غَٰفِلِينَ ١٤٦ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَلِقَآءِ ٱلۡأٓخِرَةِ حَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡۚ هَلۡ يُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٤٧

146. Zan kautar da waɗanda suke yin girman kai a bayan ƙasa ba tare da haƙƙi ba daga (fahimtar) ayoyina; idan kuma za su ga kowace irin aya ba za su yi imani da ita ba, idan kuma da za su ga hanyar shiriya ba za su riƙe ta hanyar bi ba, (amma) idan kuwa za su ga hanyar ɓata, to za su riƙe ta hanyar bi. Wannan kuwa saboda sun ƙaryata ayoyinmu, kuma sun kasance gafalallu ga barin su.

147. Waɗanda kuma suka ƙaryata ayoyinmu da haɗuwa a ranar alƙiyama, ayyukansu sun rushe. Shin kuwa za a yi musu wani sakamako ne in ba abin da suka kasance suna aikatawa ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗin cewa, zai nesanta duk waɗanda suke girman kai a bayan ƙasa ba da wani dalili ba daga fahimtar ayoyinsa; idan kuma suka ga duk wata hujja mai nuna Allah ne kaɗai ya cancanta a bauta masa, ba za su yi imani da ita ba. Hakanan idan suka ga hanyar shiriya da gyaruwa ba za su yarda su bi ta ba, amma idan suka ga hanyar ɓata da lalacewa, to za su bi ta su riƙe ta. Hakan ya faru da su ne saboda sun ƙaryata ayoyin Allah, kuma sun kasance gafalallu daga gare su. Sannan ya bayyana cewa, waɗanda suka ƙaryata ayoyinsa, suka ƙi ba da gaskiya da ranar lahira da haɗuwa da shi a lahira, to duk ayyukansu sun ɓaci, kuma ba za a saka musu da komai ba sai da munanan ayyukan da suka yi a nan duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffantu da siffar magana, domin rashin yin magana alama ce ta tawaya, domin wanda ba ya magana ta yaya zai shiryar da wani zuwa ga hanyar gaskiya? Don haka wanda duk ya ƙaryata siffantuwar Allah da magana, to ya kafirta.

2. Duk da irin mu'ujizoji daban-daban da Banu Isra'ila suka gani daga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), wannan bai sa su sun gane Ɗayantakar Allah ba, bai wanke musu ƙazantar shirka da ke cikin zukatansu ba, wadda suka kwaso daga Fir'auna da mutanensa.

Suratul A'araf (148-149)

وَٱتَّخَذَ قَوۡمُ مُوسَىٰ مِنۢ بَعۡدِهِۦ مِنۡ حُلِيِّهِمۡ عِجۡلٗا جَسَدٗا لَّهُۥ خُوَارٌۚ أَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّهُۥ لَا يُكَلِّمُهُمۡ وَلَا يَهۡدِيهِمۡ سَبِيلًا ٱتَّخَذُوهُ وَكَانُواْ ظَٰلِمِينَ ١٤٨
وَلَمَّا سُقِطَ فِيٓ أَيۡدِيهِمۡ وَرَأَوۡاْ أَنَّهُمۡ قَدۡ ضَلُّواْ قَالُواْ لَئِن لَّمۡ يَرۡحَمۡنَا رَبُّنَا وَيَغۡفِرۡ لَنَا لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ١٤٩

148. Mutanen Musa kuma a bayansa sun ƙera wani ɗan maraƙi daga kayan adonsu mai surar jiki yana wata ƙara (don su bauta masa). Shin ba su ga cewa ba ya yi musu Magana ba, kuma ba ya iya shiryar da su wani tafarki? Sun riƙe shi (a matsayin abin bauta), kuma sun tabbata azzalumai.

149. Kuma lokacin da suka yi nadama, suka gane cewa sun ɓata, sai suka ce: “Matuƙar Ubangijinmu bai ji ƙan mu ba, kuma bai gafarta mana ba, lalle za mu kasance cikin hasararru.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana abin da ya faru ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da ya tafi domin ganawa da Allah kamar yadda ya yi masa alƙawari, ya bar Banu-Isra’ila tare da ɗan’uwansa Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai mutanensa suka ƙera wani ɗan maraƙi daga kayan adonsu na gwalagwalai, wanda suka samu daga mutanen Fir’auna. Wannan ɗan maraƙi jiki ne ba mai rai ba, amma yana fitar da wani sauti kamar yana kukan maraƙi, sai suka riƙa bauta masa ba Allah ba. To amma su ba sa ganin ba ya iya yi musu magana, kuma ba ya nuna musu wata shiriya ko wani aikin alheri? Sun riƙe shi abin bauta, suka kuwa zamo azzalumai da suka cuci kawunansu suna sane.
To bayan sun yi nadama mai tsanani a kan bautar ɗan maraƙi da suka yi, suka kuma gane cewa sun ɓata, sun kauce hanyar da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bar su a kanta, to sai suka roƙi Allah gafararsa da rahamarsa, suna masu cewa, idan har Allah bai yi musu rahama ya kuma gafarta musu zunubbansu ba, to lalle za su tabbata cikin hasararru duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba zai taɓa jefar da allunan Attaura da gangan ba, bayan ya san cewa a cikinsu akwai maganar Allah. Hakanan ba zai taɓa damƙar gashin kan ɗan’uwansa Annabi Haruna da gemunsa da gangan ba. Abin da ya kai shi ga aikata waɗannan abubuwa shi ne tsananin fushi da ɓacin rai; saboda haka ne Allah ya yi masa uzuri, bai kama shi da laifin da ya aikata ba, domin yana cikin wani fushi ne wanda ya fi ƙarfinsa. Don haka abin da ya wakana a wannan lokacin ba da zaɓinsa ne ko da yardarsa ya wakana ba.

2. Duk mai yi wa Allah ƙage ko ya shigar da ƙagaggun abubuwa cikin addininsa, to yana da wani kaso na fushin Allah da wulaƙanci a rayuwarsa ta duniya. Wannan kuwa yana nuna munin bidi’a a addini.

3. Duk laifin da mutum zai yi wa Allah, babba ne ko ƙarami, idan har ya tuba, ya yi nadama, to Allah zai karɓi tubansa ya yafe masa. Wannan babban albishiri ne ga masu aikata laifukan da suke so su tuba.

Suratul A’araf (150-153)

وَلَمَّا رَجَعَ مُوسَىٰٓ إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ غَضۡبَٰنَ أَسِفٗا قَالَ بِئۡسَمَا خَلَفۡتُمُونِي مِنۢ بَعۡدِيٓۖ أَعَجِلۡتُمۡ أَمۡرَ رَبِّكُمۡۖ وَأَلۡقَى ٱلۡأَلۡوَاحَ وَأَخَذَ بِرَأۡسِ أَخِيهِ يَجُرُّهُۥٓ إِلَيۡهِۚ قَالَ ٱبۡنَ أُمَّ إِنَّ ٱلۡقَوۡمَ ٱسۡتَضۡعَفُونِي وَكَادُواْ يَقۡتُلُونَنِي فَلَا تُشۡمِتۡ بِيَ ٱلۡأَعۡدَآءَ وَلَا تَجۡعَلۡنِي مَعَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٥٠ قَالَ رَبِّ ٱغۡفِرۡ لِي وَلِأَخِي وَأَدۡخِلۡنَا فِي رَحۡمَتِكَۖ وَأَنتَ أَرۡحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ١٥١ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ ٱلۡعِجۡلَ سَيَنَالُهُمۡ غَضَبٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَذِلَّةٞ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُفۡتَرِينَ ١٥٢ وَٱلَّذِينَ عَمِلُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ ثُمَّ تَابُواْ مِنۢ بَعۡدِهَا وَءَامَنُوٓاْ إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعۡدِهَا لَغَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٥٣

150. Lokacin kuma da Musa ya dawo wajen mutanensa a fusace yana mai damuwa, sai ya ce: “Tir da abin da kuka aikata bayana. Yanzu kwa gaggauto al’amarin Ubangijinku?” Sai ya jefar da allunan, ya kama kan ɗan’uwansa yana jan sa zuwa gare shi. Sai (Haruna) ya ce: “Ya kai ɗan’ummata, mutanen nan

haƙiƙa sun raina ni, har ma sun kusa kashe ni, don haka kar ka sa maƙiya su yi min dariya, kuma kada ka sa ni cikin mutane azzalumai."

151. Sai ya ce: "Ya Ubangijina, Ka gafarta mini ni da ɗan'uwana, kuma Ka shigar da mu cikin rahamarka; kuma Kai ne Fiyayyen masu jin ƙai."

152. Lalle waɗannan da suka riƙi ɗan maraƙi (abin bauta) fushin Ubangijinsu zai same su da ƙasƙanci a cikin rayuwar duniya. Kuma kamar haka ne Muke saka wa masu ƙage.

153. Waɗanda kuma suka aikata munanan ayyuka, sannan suka tuba daga baya, kuma suka yi imani, lalle Ubangijinka bayansa (tuban), tabbas Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba mu labarin lokacin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya dawo daga wajen ganawa da Ubangijinsa, bayan ya sanar da shi cewa, Assamiri ya ɓatar da mutanensa, domin ya ƙera musu ɗan maraƙi sun shiga bautar sa ka'in-da-na'in. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya dawo a fusace sosai, yana zargin mutanensa cewa, Allah wadaran abin da suka tsiri aikatawa a bayansa, yana cewa; yanzu sa gaggauto komowarsa gare su daga ganawa da Allah kafin cikar lokacin da Allah ya sanya su gana a cikinta? Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya jefar da allunan Attaura da suke hannunsa cikin tsananin fushi da ɓacin rai, ya damƙi gashin kan ɗan'uwansa Haruna da gemunsa yana ja. Sai Haruna ya ce masa: "Ya ɗan'ummata, mutanen nan fa sun riga sun raina ni, har ma sun kusa kashe ni, don haka kada ka sa maƙiyana su riƙa yi mini dariya saboda sun ga kana duka na, kana tozarta ni, kuma kada ka sanya ni cikin waɗannan mutanen azzalumai."
To daga nan ne sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) jikinsa ya yi sanyi, ya saki ɗan'uwansa, yana roƙon Allah ya gafarta musu shi da ɗan'uwansa, kuma ya shigar da su cikin rahamarsa, domin shi ne Fiyayyen masu jin ƙai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Gani ya kori ji. Allah ya sanar da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) abin da mutanensa suka yi na bautar ɗan maraƙi, amma bai jefar da alluna ba, sai da ya ga abin da suka aikata da idonsa ne sai nan take ya jefar da su." [Ahmad #2447].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, waɗanda suka bauta wa ɗan maraƙi da sannu fushinsa zai auka musu da wulaƙanci a rayuwarsu ta duniya, kuma da irin haka zai saka wa duk masu ƙage a addini. Waɗanda kuma suka yi munanan ayyuka sannan suka tuba suka koma ga Allah, suka yi nadamar abin da suka aikata, suka yi imani da Allah da Manzonsa, to bayan wannan Allah zai gafarta musu, ya ji ƙan su, domin shi mai gafara ne, mai jin ƙai.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah mai girma da buwaya ya ce: "Ya kai ɗan'adam, lalle kai duk sa'adda ka roƙe ni, ko ka yi fata daga gare ni, to zan gafarta maka tare da abin da ya kasance na halayyarka, ban damu ba. Ya kai ɗan'adam, da zunubbanka za su taɓo girgije a sama, sannan ka nemi gafara, to da na gafarta maka, kuma ban damu ba. Ya kai ɗan'adam, da za ka zo mini da laifuffuka cikin ƙasa, sannan ka sadu da ni ba ka haɗa komai da ni a wajen bauta ba, da kuwa na zo maka da gafara cikin ƙasa." [Tirmizi #3540].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tushen samun alherin duniya da na lahira shi ne tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Wawaye su ne masu bautar ɗan maraƙi, don haka duk wanda ya yi shirka da Allah, wannan wawa ne marar hankali.

3. Dole ne Allah ya jarrabi mutane domin tantance masu gaskiya daga cikinsu da marasa gaskiya.

4. Duk wani Musulmi ko wani kafiri ko mai tsoron Allah ko marar tsoron Allah, yana birgima ne cikin ni'imomin Allah Ta'ala a nan duniya.

5. An keɓance zakka da ambato, ba a ambaci salla ba da sauran ayyukan ibada, domin fitinar son dukiya a hankalce tana hukunta cewa, masu hana zakka sun fi masu barin salla yawa.

6. Duk wani abu mai tsarki mai daɗi Allah ya halatta wa wannan al'umma amfanuwa da shi. Duk wani abu marar tsarki ko mai cutarwa Allah ya haramta wa wannan al'umma amfanuwa da shi. Lafiyayyen hankali shi ne ma'aunin gane mai tsarki da marar tsarki.

7. Addinin Musulunci addini ne mai sauƙi babu matsawa a cikinsa.

8. Nuni zuwa ga falalar sahabban Annabi (ﷺ) waɗanda suka yi imani da shi, suka taimake shi, suka girmama shi. Allah kuma ya tabbatar musu da rabo mai girma a lahira.

9. Babu mai samun rabauta sai wanda ya bi Annabi (ﷺ), ya yi koyi da shi, ya yi riƙo da sunnoninsa (ﷺ).

Suratul A'araf (154-157)

وَلَمَّا سَكَتَ عَن مُّوسَى ٱلْغَضَبُ أَخَذَ ٱلْأَلْوَاحَ ۖ وَفِى نُسْخَتِهَا هُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلَّذِينَ هُمْ لِرَبِّهِمْ يَرْهَبُونَ ﴿١٥٤﴾ وَٱخْتَارَ مُوسَىٰ قَوْمَهُۥ سَبْعِينَ رَجُلًا لِّمِيقَٰتِنَا ۖ فَلَمَّآ أَخَذَتْهُمُ ٱلرَّجْفَةُ قَالَ رَبِّ لَوْ شِئْتَ أَهْلَكْتَهُم مِّن قَبْلُ وَإِيَّىَّ ۖ أَتُهْلِكُنَا بِمَا فَعَلَ ٱلسُّفَهَآءُ مِنَّآ ۖ إِنْ هِىَ إِلَّا فِتْنَتُكَ تُضِلُّ بِهَا مَن تَشَآءُ وَتَهْدِى مَن تَشَآءُ ۖ أَنتَ وَلِيُّنَا فَٱغْفِرْ لَنَا وَٱرْحَمْنَا ۖ وَأَنتَ خَيْرُ ٱلْغَٰفِرِينَ ﴿١٥٥﴾ ۞ وَٱكْتُبْ لَنَا فِى هَٰذِهِ ٱلدُّنْيَا حَسَنَةً وَفِى ٱلْءَاخِرَةِ إِنَّا هُدْنَآ إِلَيْكَ ۚ قَالَ عَذَابِىٓ أُصِيبُ بِهِۦ مَنْ أَشَآءُ ۖ وَرَحْمَتِى وَسِعَتْ كُلَّ شَىْءٍ ۚ فَسَأَكْتُبُهَا لِلَّذِينَ يَتَّقُونَ وَيُؤْتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱلَّذِينَ هُم بِـَٔايَٰتِنَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٥٦﴾ ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ ٱلرَّسُولَ ٱلنَّبِىَّ ٱلْأُمِّىَّ ٱلَّذِى يَجِدُونَهُۥ مَكْتُوبًا عِندَهُمْ فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ وَٱلْإِنجِيلِ يَأْمُرُهُم بِٱلْمَعْرُوفِ وَيَنْهَىٰهُمْ عَنِ ٱلْمُنكَرِ وَيُحِلُّ لَهُمُ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَيُحَرِّمُ عَلَيْهِمُ ٱلْخَبَٰٓئِثَ وَيَضَعُ عَنْهُمْ إِصْرَهُمْ وَٱلْأَغْلَٰلَ ٱلَّتِى كَانَتْ عَلَيْهِمْ ۚ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِهِۦ وَعَزَّرُوهُ وَنَصَرُوهُ وَٱتَّبَعُوا۟ ٱلنُّورَ ٱلَّذِىٓ أُنزِلَ مَعَهُۥٓ ۙ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿١٥٧﴾

154. Yayin kuma da Musa ya huce, sai ya ɗauki allunan nan (na Attaura); kuma abin da aka rubuta a cikinsu shiriya ne da rahama ga waɗanda suke tsoron Ubangijinsu.

155. Musa kuma ya zaɓi mutanensa, maza (na musamman) su saba'in don alƙawarinmu; to yayin da wata tsawa ta kama su, sai ya ce: "Ya Ubangijina, idan da Ka ga dama da tun tuni Ka hallakar da su har da ni kaina. Yanzu Ka halaka mu saboda abin da wasu wawaye daga cikinmu suka aikata? Lalle wannan ba komai ba ne face jarrabawa daga gare Ka, Kana ɓatar da wanda Ka ga dama; Kana kuma shiryar da wanda Ka ga dama; Kai ne Majiɓincin lamarinmu, don haka Ka gafarta mana, kuma Ka ji ƙan mu, kuma Kai ne Fiyayyen masu gafara.

156. "Kuma Ka rubuta mana kyakkyawan abu a cikin wannan duniyar, haka ma a lahira, lalle mu mun tuba zuwa gare Ka." (Allah) Ya ce: "Ina saukar da azabata a kan wanda Na ga dama; rahamata kuwa ta

yalwaci komai. Don haka da sannu zan rubuta ta ga waɗanda suke kiyaye dokokin Allah, kuma suke bayar da zakka da kuma waɗanda suke yin imani da ayoyinmu.

157. “(Su ne) waɗanda suke bin Manzo Annabi Ummiyyi, wanda suke samun sa a rubuce a wurinsu a cikin Attaura da Linjila, yana umartar su da kyakkyawan abu, kuma yana hana su mummuna, kuma yana halatta musu daɗaɗan abubuwa, yana kuma haramta musu ƙazantattu, kuma yana sauke musu nauyaye-nauyayensu da ƙuƙumce-ƙuƙumcen da suka kasance a kansu. Don haka waɗanda suka yi imani da shi, kuma suka ƙarfafe shi, suka kuma taimake shi, suka bi hasken da aka saukar tare da shi, waɗannan su ne masu rabauta.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan da ya huce daga fushin da ya yi saboda bautar ɗan maraƙi da mutanensa suka yi, sai ya ɗauki allunan littafin Attaura waɗanda ya jefar, waɗanda kuma a cikinsu akwai shiriya daga ɓata da rahama ga masu jin tsoron Ubangijinsu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake yin wani alƙawarin haɗuwa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), amma a wannan karon ya umarce shi da ya zaɓi mutum saba’in daga Banu Isra’ila ya je ganawar da su. Malamai sun yi saɓani a kan dalilin wannan tafiya da su, amma zance mafi karɓuwa shi ne don su gabatar da uzurinsu game da bautar ɗan maraƙi da suka yi, su nemi gafarar Allah, a kansu da kuma ‘yan’uwansu da ba a zo da su ba.
Wasu malaman kuma sun ce ya je da su ne karɓar Littafin Attaura, wasu kuma sun ce ya tafi da sun ne domin su yi addu’a, wasu kuma cikinsu cewa suka yi, saboda an samu wasu daga cikin Banu-Isra’ila da suka nuna ba su yarda cewa, Allah ya yi magana da Annabi Musa ba, idan har haka gaskiya ne, to su ma lalle ya tafi da su don su ji maganar Allah da kunnuwansu, sannan su yarda da shi su daina zargin sa. Sheikh Asshanƙiɗi ya ce: “Akwai maganganu da yawa irin waɗannan, amma ba su da wani dalili.” [*Al-‘Azbun Namir*, Juzu’i na 4, Shafi na 193].
To bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da jama’arsa sun isa wajen dutsen Ɗuri Sina sai wata girgiza mai tsanani ta kama su. Masana a nan ma sun yi maganganu daban-daban game da dalilin wannan girgiza; wasu suka ce saboda sun ƙi su daina bautar ɗan maraƙi ne, wasu kuma suka ce saboda sun tuhumi Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kisan ɗan’uwansa Annabi Haruna, wasu kuma cewa suka yi saboda sun wuce gona da iri wajen addu’a, yayin da wasu malaman cewa suka yi saboda sun ji maganar Allah amma sai suka ce wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) su ba su yarda ba har sai sun ga Allah da idanuwansu a fili, kamar yadda ya zo a *Suratul Baƙara,* aya ta 55-56. [Ibnul Jauzi, *Zadul Masir*, Juzu’i na 2, Shafi na 158-159].
Sheikh Asshanƙiɗi ya kawo waɗannan maganganu, amma daga ƙarshe ya ce: “Duk waɗannan maganganun malaman tafsiri ne, akwai ma wasu ban da waɗannan, babu wani dalili mai yanke shakka a kansu. Allah Ta’ala ne mafi sani.” [*Al-Azbun Namir*, Juzu’i na 4, Shafi na 195-196].
Da girgiza ta kama zaɓaɓɓun mutanen nan su saba’in, sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙi Ubangijinsa cewa: “Ya Ubangijina, da ka ga dama da sai ka halakar da su kafin wannan lokaci, ni ma ka karɓi raina tare da su kuma a gaban sauran ‘yan’uwansu don kada su tuhume ni da cewa ni ne na kashe musu ‘yan’uwa. Ya Allah, yanzu ka halaka mu saboda abin da wasu wawaye daga cikinmu suka aikata na bautar ɗan maraƙi? Bautar ɗan maraƙi da wawaye daga cikinmu suka yi ba komai ne ba sai jarraba daga gare ka; kana ɓatar da wanda ka ga dama da ita, ka shiryar da wanda ka ga dama. Kai ne mai taimakon mu, mai jiɓintar al’amuranmu, don haka ka gafarta mana, ka ji ƙan mu, kai ne Fiyayyen masu gafara, ka rubuta mana abu mai kyau a nan duniya, hakanan ma a lahira, haƙiƙa mu mun tuba zuwa gare ka.”
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa, azabarsa a nan duniya yana saukar da ita ga wanda ya ga dama, rahamarsa a duniya kuma ta yalwaci duk

halittarsa, don haka da sannu zai tabbatar da ita ga waɗanda suke kiyaye dokokinsa, suke kuma fidda zakka, suka yi imani da ayoyinsa, suke bin Annabi Muhammadu (ﷺ) sau-da-ƙafa. Annabin da ba ya ƙaratu da rubutu, wanda suke ganin siffofinsa a cikin Attaura da Linjila, yana umartar su da kyakkyawan aiki, yana hana su mummuna, yana halatta musu daɗaɗan abubuwa, yana haramta musu munana, kuma yana sauke musu nauyaye-nauyayen abubuwa masu wuya da aka wajabta musu aiki da su a littafin Attaura, da abubuwan da aka tsananta musu haramcinsu masu kama da ƙuƙumi a wuyayensu. Don haka waɗanda suka yi imani da shi, suka girmama shi, suka taimake shi, suka bi Alƙur'anin da Allah ya saukar masa, to waɗannan su ne masu samun babban rabo a duniya da lahira.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru ya ce: Wallahi an siffanta Annabi Muhammadu (ﷺ) a Attaura da wasu siffofinsa da suka zo a Alƙur'ani, an kirawo shi: "Ya kai wannan Annabi, lalle mu mun aiko ka don ka zama mai shaida, mai albishir, kuma mai gargaɗi, ka zamo kariya ga Larabawa ummiyyai. Kai bawana ne kuma manzona, na raɗa maka suna Al-*Mutawakkilu* (wato mai dogaro ga Allah), shi ba mai kakkausan hali ba ne, ba mai ƙeƙasasshiyar zuciya ba, ba mai hayaniya a kasuwanni ba, ba ya rama mugunta da mugunta, sai dai ya yi afuwa, ya yi gafara. Allah ba zai karɓi ransa ba har sai ya miƙar da karkataccen addini da shi, wato su ce: Babu abin bauta da gaskiya sai Allah. Ya kuma buɗe makafin idanuwa da kuramen kunnuwa da rufaffun zukata da wannan Kalma ta Shahada." [Bukhari #4838].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda rayuwa da mutuwa take a hannunsa shi ne babban wanda ya kamata a ji tsoro, don babu wani abu da zai sami mutum a duniya da ya kai mutuwa wadda za ta raba shi da komai. Babu wani aiki mai girma da ya kai tayar da matacce bayan ya zama rududdugaggun ƙasusuwa. Tsarki ya tabbata ga Allah mahaliccin komai.

2. Dole ne duk mai kira zuwa ga wani abu ya fara yin imani da abin da yake kira zuwa gare shi, ya kuma samu yaƙini da tabbaci a zuciyarsa game da da'awarsa.3. Babu wanda zai samu shiriya sai wanda ya bi Annabi (ﷺ).

4. Babu wanda yake da haƙƙin kafa shari'a da halattawa da haramtawa sai wanda shi ne mamallakin sammai da ƙasa, wanda rayuwa da mutuwa duka suke a hannunsa, wato Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Kalmomin Allah waɗanda Annabi (ﷺ) ya yi imani da su sun ƙunshi kalmominsa na shari'a, wato ayoyinsa da hukunce-hukuncensa da kuma kalmominsa na halitta waɗanda suka haɗa da abubuwan da yake ƙaddara faruwarsu, masu daɗi da marasa daɗi, waɗanda wajibi ne bawa ya sallama wa Ubangijinsa, ya miƙa wuya.

Suratul A'araf (158)

قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنِّى رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُمْ جَمِيعًا ٱلَّذِى لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ يُحْىِۦ وَيُمِيتُ ۖ فَـَٔامِنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِ ٱلنَّبِىِّ ٱلْأُمِّىِّ ٱلَّذِى يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَكَلِمَٰتِهِۦ وَٱتَّبِعُوهُ لَعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ﴿١٥٨﴾

158. Ka ce: "Ya ku mutane, lalle ni Manzon Allah ne zuwa gare ku gaba ɗaya, wanda Yake da mallakar sammai da ƙasa, babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi; Shi ne Yake rayawa, kuma Shi Yake kashewa;

don haka ku yi imani da Allah da Manzonsa Annabi Ummiyyi, wanda yake yin imani da Allah da kalmominsa, kuma ku bi shi don ku zama shiryayyu.”

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa mutane gaba ɗaya cewa, shi Manzon Allah ne zuwa gare su baki ɗaya. Kuma Allah wanda ya aiko shi shi ne mamallakin sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu; babu abin bauta wa da gaskiya sai shi, yana rayawa yana kashewa, don haka su yi imani da Allah da Manzonsa Muhammadu (ﷺ) wanda shi ne Annabi Ummiyyi, wato ba ya ƙaratu ba ya rubutu, shi ne wanda yake yin imani da Allah da kalmominsa, kuma lalle su bi shi ko sa samu shiriya.

An karɓo daga Jabiru ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “An ba ni abubuwa biyar waɗanda ba a ba wa wani annabi su ba gabanina: An taimake ni da jefa tsoro a zukatan maƙiyana tun daga tazarar tafiyar wata ɗaya; kuma an sanya mini bayan ƙasa ya zama wurin salla da tsarki, kowane mutum a cikin al’ummata da salla za ta riske shi a ko’ina ne, to ya sallace ta; an halatta mini cin ganima; kowane annabi ya kasance ana aiko shi ne zuwa ga mutanensa kaɗai, to amma ni an aiko ni ne zuwa ga mutane gaba ɗaya; kuma an ba ni ceto ranar alƙiyama.” [Bukhari #438, da Muslim #521].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Na rantse da wanda ran Muhammadu yake a hannunsa, ba wani daga cikin wannan al’umma da zai samu labarina, Bayahude ne ko Banasare, sannan har ya mutu bai yi imani da abin da aka aiko ni da shi ba, sai ya zamo cikin ‘yan wuta.” [Muslim #153].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur’ani littafi ne mai cike da adalci. Al’ummar da take da girma, abu ne mai wuya a rasa mutanen kirki a cikinta, don haka sai Alƙur’ani bai yi wa Banu-Isra’ila kuɗin goro ba.

2. Idan mutum ya saɓa wa Allah, to bai cuci kowa ba kansa ya cuta, domin ya jawo wa kansa uƙuba ne.

Suratul A’araf (159-160)

وَمِن قَوۡمِ مُوسَىٰٓ أُمَّةٞ يَهۡدُونَ بِٱلۡحَقِّ وَبِهِۦ يَعۡدِلُونَ ١٥٩ وَقَطَّعۡنَٰهُمُ ٱثۡنَتَيۡ عَشۡرَةَ أَسۡبَاطًا أُمَمٗاۚ وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ إِذِ ٱسۡتَسۡقَىٰهُ قَوۡمُهُۥٓ أَنِ ٱضۡرِب بِّعَصَاكَ ٱلۡحَجَرَۖ فَٱنۢبَجَسَتۡ مِنۡهُ ٱثۡنَتَا عَشۡرَةَ عَيۡنٗاۖ قَدۡ عَلِمَ كُلُّ أُنَاسٖ مَّشۡرَبَهُمۡۚ وَظَلَّلۡنَا عَلَيۡهِمُ ٱلۡغَمَٰمَ وَأَنزَلۡنَا عَلَيۡهِمُ ٱلۡمَنَّ وَٱلسَّلۡوَىٰۖ كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقۡنَٰكُمۡۚ وَمَا ظَلَمُونَا وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ١٦٠

159. Kuma daga cikin mutanen Musa akwai wata jama’a waɗanda suke shiryarwa da gaskiya, da kuma ita ne suke yin hukunci na adalci.

160. Mun kuma karkasa su ƙabilu goma sha biyu daban-daban, sai Muka kuma yi wahayi ga Musa yayin da mutanensa suka nemi ya shayar da su ruwa cewa: “Ka doki dutse da sandarka,” sai idanun ruwa goma sha biyu suka ɓuɓbugo daga jikinsa. Haƙiƙa kowace ƙabila ta san mashayarta. Muka kuma yi musu inuwa da girgije, kuma Muka saukar musu da darɓa da tsuntsayen salwa; (muka ce:) “Ku ci daga daddaɗan abin da Muka arzurta ku da shi.” Kuma ba su zalunce Mu ba, sai dai kansu suka kasance suna zalunta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa daga cikin mutanen Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) akwai na kirki waɗanda suke shiryuwa da gaskiyar da Allah ya aiko shi da ita, kuma suna yin hukunci a tsakaninsu da ita kuma su yi adalci, don haka ba su taru sun zama ɗaya ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin yadda ya karkasa Banu-Isra'ila gidaje har goma sha biyu, kowane gida a matsayin ƙabila mai zaman kanta, domin hakan zai taimaka wajen gudanar da harkokin shugabanci a cikin kowace ƙabila. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wahayi lokacin da mutanensa suka neme shi ya yi musu roƙon ruwa a daidai lokacin da suke cikin ɗimuwarsu a saharar Sina'a. Allah ya umarce shi da ya doki wani dutse da sandarsa, sai ya yi hakan, nan take kuma idanuwan ruwa goma sha biyu suka ɓuɓbugo, daga nan kowace ƙabila ta gane idon ruwan da yake shi ne mashayarta, wanda su kaɗai za su yi amfani da shi wajen shan ruwa da wanka da wanki.
Bayan wannan ni'imar kuma, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Banu Isra'ila wata ni'imar ta biyu, watau ya yi musu inuwa da girgije don ba su kariya daga tsananin zafin ranar sahara. Bugu da ƙari kuma ya saukar musu da darɓa da soyayyun tsuntsayen salwa, ya umarce su da su ci daddaɗan abin da Allah ya arzuta su da shi. To amma maimakon su gode wa Allah, sai suka saɓa wa umarninsa, to sai dai ba Allah suka zalunta ba da wannan ɗanyen aiki nasu, domin saɓon masu saɓo ba ya cutar da Allah da komai; kawunansu kaɗai suka zalunta don sun yi hasarar rabonsu na duniya da na lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin zalunci, canza maganar Allah ko umarninsa da wani abu na daban.

2. Duk al'ummar da ba ta guji zalunci ba, to ƙarshenta Allah ya saukar mata da uƙubarsa tun a duniya kafin ta lahira.

3. Samuwar mutanen ƙwarai a cikin ɗimbin masu laifi ba za ta kare musu azabar Allah ba.

Suratul A'araf (161-162)

وَإِذْ قِيلَ لَهُمُ ٱسْكُنُواْ هَٰذِهِ ٱلْقَرْيَةَ وَكُلُواْ مِنْهَا حَيْثُ شِئْتُمْ وَقُولُواْ حِطَّةٌ وَٱدْخُلُواْ ٱلْبَابَ سُجَّدًا نَّغْفِرْ لَكُمْ خَطِيٓـَٔتِكُمْ ۚ سَنَزِيدُ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿١٦١﴾ فَبَدَّلَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنْهُمْ قَوْلًا غَيْرَ ٱلَّذِى قِيلَ لَهُمْ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِجْزًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُواْ يَظْلِمُونَ ﴿١٦٢﴾

161. Kuma ka tuna lokacin da aka ce musu: "Ku zauna a wannan alƙarya, kuma ku ci daga gare ta a duk inda kuka ga dama, ku kuma ce: *Hiddɑ* (wato Allah Ka share mana laifukanmu), ku kuma shiga ta ƙofar alƙaryar kuna masu sujjada, za Mu gafarta muku zunubanku, kuma za Mu ƙara wa masu kyautatawa."

162. Sai waɗanda suka yi zalunci a cikinsu suka canja magana daban da wadda aka faɗa musu, sai Muka aiko musu da wata azaba daga sama, saboda abin da suka kasance suna yi na zalunci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayani ne game da umarnin da ya ba wa Banu-Isra'ila na shiga garin Baitil Maƙadis bayan sun fito daga Masar, ya umarce su da su ci daga 'ya'yan itatuwan wannan gari da tsirransa a duk inda suke so, ya kuma umarce su da su nemi gafarar Allah lokacin da suke shiga garin, kuma su shiga a sunkuye suna masu ƙasƙantar da kansu ga Allah (Mai tsarki

da ɗaukaka). Ya yi musu alƙawarin zai gafarta musu zunubansu idan har sun aikata hakan, sannan wanda ya kyautata daga cikinsu, zai ƙara masa ladansa.
To amma saboda zaluncin Banu-Isra'ila ga kawunansu sai suka canza wannan umarni na Allah; maimakon su nemi gafarar Allah, sai suka riƙa cewa: "Kwaya a cikin gashi." sannan suka shiga garin suna jan gindi. Sakamakon haka sai Allah ya saukar musu da azaba daga sama saboda zaluntar kansu da suka riƙa yi ta hanyar aikata saɓon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya yi wa Allah ɗa'a, to zai kawo masa sauƙi cikin duk lamurransa na duniya da na lahira. Wanda kuwa ya saba wa Allah, to zai jarrabe shi da bala'i iri-iri tun a nan duniya kafin ya je lahira.

2. Umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna wajibi ne a cikin al'umma.

3. Idan uƙubar Allah ta sauka, masu umarni da kyakkyawa da hana mummuna sune masu samun tsira daga gare ta.

4. Waɗannan ayoyi sun yi bayanin amfanin wa'azi a cikin al'umma, kamar haka:
• Gabatar da uzuri a gaban Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bayan mutum ya yi bakin ƙoƙarinsa wajen faɗakarwa.
• Fatan wanda ake yi wa wannan wa'azi ya karɓi wa'azin ya gyara halinsa.
• Tsayar da hujjar Allah a kan kowa, kamar yadda annabawa suka yi, hakanan su ma malamai za su yi domin suna wakiltar su ne a bayansu.

5. Allah ya shafe halittar masu laifi na Banu Isra'ila ya mayar da su birrai, domin biri ya yi kama da mutum a zahiri, amma shi ba mutum ne ba. Hakanan ayyukan waɗannan mutane yayin da a zahiri suke kama da ayyukan ƙwarai, amma a haƙiƙa ba na ƙwarai ba ne, sai sakamakonsu ya zamo irin aikinsu.

Suratul A'araf (163-166)

وَسْـَٔلْهُمْ عَنِ ٱلْقَرْيَةِ ٱلَّتِى كَانَتْ حَاضِرَةَ ٱلْبَحْرِ إِذْ يَعْدُونَ فِى ٱلسَّبْتِ إِذْ تَأْتِيهِمْ حِيتَانُهُمْ يَوْمَ سَبْتِهِمْ شُرَّعًا وَيَوْمَ لَا يَسْبِتُونَ لَا تَأْتِيهِمْ ۚ كَذَٰلِكَ نَبْلُوهُم بِمَا كَانُوا۟ يَفْسُقُونَ ﴿١٦٣﴾ وَإِذْ قَالَتْ أُمَّةٌ مِّنْهُمْ لِمَ تَعِظُونَ قَوْمًا ٱللَّهُ مُهْلِكُهُمْ أَوْ مُعَذِّبُهُمْ عَذَابًا شَدِيدًا ۖ قَالُوا۟ مَعْذِرَةً إِلَىٰ رَبِّكُمْ وَلَعَلَّهُمْ يَتَّقُونَ ﴿١٦٤﴾ فَلَمَّا نَسُوا۟ مَا ذُكِّرُوا۟ بِهِۦٓ أَنجَيْنَا ٱلَّذِينَ يَنْهَوْنَ عَنِ ٱلسُّوٓءِ وَأَخَذْنَا ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ بِعَذَابٍۭ بَـِٔيسٍۭ بِمَا كَانُوا۟ يَفْسُقُونَ ﴿١٦٥﴾ فَلَمَّا عَتَوْا۟ عَن مَّا نُهُوا۟ عَنْهُ قُلْنَا لَهُمْ كُونُوا۟ قِرَدَةً خَـٰسِـِٔينَ ﴿١٦٦﴾

163. Kuma ka tambaye su game da (mutanen) alƙaryar nan wadda take dab da gaɓar teku, yayin da suke ƙetare iyaka a ranar Asabar, yayin da kifayensu suke zuwa a ranar Asabar baja-baja, amma ranar da ba Asabar ba kuwa ba sa zuwa. Kamar haka ne muka jarrabe su saboda abin da suka kasance suna yi na fasiƙanci.

164. Kuma ka tuna lokacin da wata jama'a cikinsu suka ce: "Don me za ku riƙa wa'azi ga waɗansu mutanen da idan Allah Ya ga dama sai Ya hallakar da su ko Ya yi musu azaba mai tsanani?" Sai suka ce: "Don yanke hanzari ne a wurin Ubangijinku ko watakila kuma sa kiyaye dokokin Allah."

165. To yayin da suka yi watsi da abin da aka yi musu wa'azi da shi, sai Muka tserar da waɗanda suke hana mummunan aiki, Muka kuma kama waɗanda suka yi zalunci, da wata mummunar azaba, saboda abin da suka riƙa yi na fasiƙanci.

166. To yayin da suka yi tsaurin kai a kan abin da aka hana su, sai Muka ce da su: "Ku zama birrai, ƙaskantattu."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin wata jarabawa da ya yi wa Banu-Isra'ila lokacin da ya haramta musu duk wani aiki a ranar Assabar wadda suka zaɓa su riƙa yin bauta a cikinta maimakon ranar Juma'a da Allah ya zaɓa musu da farko.
Wannan ƙissa ce daga cikin ƙissoshin Banu-Isra'ila, na wata alƙarya wadda take a gaɓar kogi, mutanenta sun shahara da fasiƙanci da rashin ɗa'a. Sana'arsu ita ce kamun kifi, sai Allah ya yi nufin ya jarrabe su don ganin ko za su kiyaye alfarmar ranar Assabar wadda aka haramta musu yin kowane irin aiki na duniya a cikinta ko ba za su kiyaye ba? Sai Allah cikin hikimarsa ya ƙaddara kifayen wannan ruwa na kusa da su ba sa fitowa da yawa sai ranar Assabar; sauran ranakun kuwa sai a ga babu su gaba ɗaya. Mutanen wannan alƙarya suka kasa haƙuri su bi dokar barin aikin ranar Assabar domin suna ganin kamun kifi a wannan rana zai samar musu da riba mai tarin yawa, sai yawancinsu suka yi wa wannan doka tawaye, suka riƙa baza komarsu ranar Assabar suna kamun kifaye.

Ganin haka sai malaman kirki daga cikinsu suka shiga yi musu wa'azi suna hana su wannan ɗanyen aikin, to amma sai suka bijire, suka ƙi saurarensu, suka ma ƙara dagewa wajen saɓa wa wannan doka. Wasu masu yin wa'azi da suka kula wa'azinsu ba ya shiga kunnuwan waɗannan mutane sai suka yanke shawarar su daina yin wa'azin. Amma wasu daga cikinsu sun ci gaba da yi musu wa'azi domin suna sa ran za su saurare su wata rana su karɓi nasiharsu su daina. Sai ɓangarorin biyu na mutanen kirki suka tattauna game da ci gaba da yin wa'azi ga kangararrun mutane, sai waɗanda suka daina yin wa'azin suka faɗa wa masu ci gaba da yin wa'azi cewa, me ya sa za su ci gaba da yin wa'azi ga mutanen da babu alamar shiryuwa tare da su, babu abin da ya rage musu sai Allah ya halaka su, ko ya yi musu azaba mai tsanani? Masu son ci gaba da yin wa'azi kuma suka amsa da cewa, suna yin wa'azin ne don yanke hanzari a gaban Allah, kuma su tabbatar sun yi iya ƙoƙarinsu wajen jawo hankulansu ko watakila za a samu masu haƙura su daina abin da suke yi na saɓon Allah.
To lokacin da waɗannan mutane masu taurin kai suka ci gaba da kangarewarsu suna kamun kifi ranar Assabar, sai Allah ya saukar musu da azabarsa, ya shafe halittarsu ta mutane, ya mayar da su birrai ƙaskantattu wulaƙantattu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tserar da waɗanda suka ci gaba da yi musu wa'azi daga wannan mummunan ƙarshen.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan jarrabi bayinsa da abu mai daɗi kamar yadda yake jarrabar su da abu marar daɗi.

2. Duk sa'adda Allah ya ambaci azabar maɓarnata a bayan ƙasa yakan haɗa da ambaton gafararsa da rahamarsa don ya nuna wa masu laifi cewa ƙofar tuba a buɗe take ga duk mai son ya tuba, Allah zai karɓi tubansa ya gafarta masa ya ji ƙan sa.

3. Abin da Allah ya tanadar wa masu tsoron sa a lahira na ni'ima ya fi duk wani jin daɗi na duniya mai ƙarewa.

4. Duk wanda Allah zai sanar da shi hukunce-hukuncensa amma ya yi watsi da su, ya fifita abin duniya a kan riƙo da shari'ar Allah, to wannan ya zama kamar Yahudawa, kuma Allah zai yi fushi da shi kamar yadda ya yi fushi da su.

5. Idan mutum yana da'awar shi Musulmi ne amma yana keta alfarmar addinin Musulunci, to wannan yana yaudarar kansa ne kawai, kuma ya ɗauki wani hali ne daga cikin halayen Yahudawa.

6. Hanyar Allah da tsarinsa a rayuwa su ne riƙon littafinsa da ƙarfi da tsayar da salla tare da haƙƙokinta. Riƙe Alƙur'ani da aiki da dokokinsa shi ne gyaruwar rayuwar ɗan'adam; tsayar da salla kuwa ita ce gyaruwar zuciyarsa.

7. Ana buƙatar duk wani mai riƙo da littafin Allah da sunnar Manzonsa ya zamanto nagari a ƙaran-kansa, kuma mai gyara wasu da koyarwarsa da da'awarsa.

Suratul A'araf (167-170)

وَإِذْ تَأَذَّنَ رَبُّكَ لَيَبْعَثَنَّ عَلَيْهِمْ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَـٰمَةِ مَن يَسُومُهُمْ سُوٓءَ ٱلْعَذَابِ ۗ إِنَّ رَبَّكَ لَسَرِيعُ ٱلْعِقَابِ وَإِنَّهُۥ لَغَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٦٧﴾ وَقَطَّعْنَـٰهُمْ فِى
ٱلْأَرْضِ أُمَمًا ۖ مِّنْهُمُ ٱلصَّـٰلِحُونَ وَمِنْهُمْ دُونَ ذَٰلِكَ ۖ وَبَلَوْنَـٰهُم بِٱلْحَسَنَـٰتِ وَٱلسَّيِّـَٔاتِ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿١٦٨﴾ فَخَلَفَ مِنۢ بَعْدِهِمْ خَلْفٌ وَرِثُوا۟
ٱلْكِتَـٰبَ يَأْخُذُونَ عَرَضَ هَـٰذَا ٱلْأَدْنَىٰ وَيَقُولُونَ سَيُغْفَرُ لَنَا وَإِن يَأْتِهِمْ عَرَضٌ مِّثْلُهُۥ يَأْخُذُوهُ ۚ أَلَمْ يُؤْخَذْ عَلَيْهِم مِّيثَـٰقُ ٱلْكِتَـٰبِ أَن لَّا يَقُولُوا۟
عَلَى ٱللَّهِ إِلَّا ٱلْحَقَّ وَدَرَسُوا۟ مَا فِيهِ ۗ وَٱلدَّارُ ٱلْـَٔاخِرَةُ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ يَتَّقُونَ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿١٦٩﴾ وَٱلَّذِينَ يُمَسِّكُونَ بِٱلْكِتَـٰبِ وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ إِنَّا لَا
نُضِيعُ أَجْرَ ٱلْمُصْلِحِينَ ﴿١٧٠﴾

167. Kuma ka tuna lokacin da Ubangijinka Ya yi shela, lalle zai aiko musu da wanda zai ɗandana musu mummunar azaba, har ya zuwa ranar tashin alƙiyama. Lalle Ubangijinka Mai gaggawar uƙuba ne, kuma lalle shi tabbas Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

168. Kuma Mun rarraba su ƙabilu daban-daban a bayan ƙasa; a cikinsu akwai salihai, kuma daga cikinsu akwai koma bayan haka; kuma Mun jarrabe su da kyawawan abubuwa da munana, don su komo (zuwa hanya).

169. Sai waɗansu bara-gurbi suka maye bayansu, sun gaji littafin (Attaura), suna karɓar abin duniya, suna kuma cewa: "Za a gafarta mana." Kuma idan wani abin duniyar irinsa ya zo musu sai su sake karɓar sa. Shin yanzu ba a ɗauki alƙawari daga wurinsu ba a cikin littafin (Attaura) cewa, kada su faɗi wata magana game da Allah sai gaskiya, kuma sun ƙaranta abin da yake cikinsa? Kuma lalle gidan lahira shi ne mafi alheri ga dukkan waɗanda suke da taƙawa. Shin ba za ku hankalta ba?

170. Waɗanda kuwa suke riƙo da Littafi, kuma suke tsayar da salla, to lalle Mu ba ma tozarta ladan masu gyara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) ya tuna lokacin da ya sanar wa Yahudawa abin da ya riga ya hukunta a kansu, wanda kuma sai ya faru da su babu makawa, wato yadda zai haɗa su da waɗanda za su yi ta gana musu azaba iri-iri a lokuta daban-daban saboda yawan saɓon Allah da zalunci da suke yi. Sun yi ta ganin haka a tsawon tarihinsu. An ce tun zamanin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sannan da zamanin sarakunan Girkawa da Kildaniyawa da lokacin sarkin Babila Bukhtanassar da kuma zamanin Manzon Allah da sahabbansa sun yi ta ganin

ƙasƙanci da wulaƙanci iri-iri, tun daga kan kakanni har zuwa jikoki har kuma alƙiyama ta tashi, ko da sun samu sun yi ƙarfi a wani lokaci, to za su zo su sake faɗawa cikin ƙasƙanci a gaba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, ya rarraba su ƙabilu daban-daban sun watsu a bayan ƙasa saboda ɓarnarsu da fasiƙancinsu da son kansu. Wasu kaɗan daga cikinsu mutanen kirki ne, wasu kuma ba haka ba. Allah ya jarrabe su jarrabawa iri-iri, wata mai kyau wata marar kyau don su koma kan daidaitacciyar hanya.
Daga baya sai wasu Yahudawa bara-gurbi suka zo suka maye gurbin magabatansu, babu alheri tare da su, ga shi sun gaji littafin Attaura daga iyayensu, sun ƙaranta abin da yake cikinsa na hukunce-hukunce, amma son duniya ce kaɗai a zukatansu, suna karɓar kuɗaɗen haram, sun yi watsi da aiki da hukunce-hukuncen Attaura, suna ruɗar kawunansu da cewa, wai Allah zai gafarta musu zunubbansu, sannan idan suka ƙara cin karo da wata dukiyar ta haram irin ta farko sai su sake karɓewa su ci. Ashe yanzu Allah bai yi alƙawari mai ƙarfi da su a cikin Attaura ba cewa, kada su faɗi wani abu su dangana shi ga Allah sai gaskiya, sun kuma ƙaranta abin da yake cikin Attaura sun fahimce shi, sun manta da cewa gidan lahira ya fi alheri ga masu kiyaye dokokin Allah, me ya sa ba za su hankalta ba?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda suke riƙe da littafinsa ƙam-ƙam, suna aiki da shi, suka kuma tsayar da salla, to waɗannan mutane ne nagari masu gyara, Allah kuwa ba ya tozarta ladansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Riƙe addini da gaske yana tsarkake zuciya daga duk wata ƙazanta da za ta same ta.

2. Wajibi ne a kan duk wanda aka sanar da shi wani hukunci na Allah da Manzonsa ya riƙe shi ƙam-ƙam, kada ya yi sakaci ko wasa da shi.

3. Idan da za a ƙyale mutum da halittarsa ta asali, to da zai tabbatar da Kaɗaitakar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da an haɗa shi da komai ba.

4. Allah ba ya yi wa kowa uƙuba da laifin da ba nasa ba.

Suratul A’araf (171-174)

*وَإِذۡ نَتَقۡنَا ٱلۡجَبَلَ فَوۡقَهُمۡ كَأَنَّهُۥ ظُلَّةٞ وَظَنُّوٓاْ أَنَّهُۥ وَاقِعُۢ بِهِمۡ خُذُواْ مَآ ءَاتَيۡنَٰكُم بِقُوَّةٖ وَٱذۡكُرُواْ مَا فِيهِ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ١٧١ وَإِذۡ أَخَذَ رَبُّكَ مِنۢ بَنِيٓ ءَادَمَ مِن ظُهُورِهِمۡ ذُرِّيَّتَهُمۡ وَأَشۡهَدَهُمۡ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ أَلَسۡتُ بِرَبِّكُمۡۖ قَالُواْ بَلَىٰۛ شَهِدۡنَآۛ أَن تَقُولُواْ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ إِنَّا كُنَّا عَنۡ هَٰذَا غَٰفِلِينَ ١٧٢ أَوۡ تَقُولُوٓاْ إِنَّمَآ أَشۡرَكَ ءَابَآؤُنَا مِن قَبۡلُ وَكُنَّا ذُرِّيَّةٗ مِّنۢ بَعۡدِهِمۡۖ أَفَتُهۡلِكُنَا بِمَا فَعَلَ ٱلۡمُبۡطِلُونَ ١٧٣ وَكَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ وَلَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ١٧٤

171. Ka tuna kuma lokacin da Muka ɗaga dutse a samansu kamar girgije, kuma suka sakankance cewa zai rikito musu, (Muka ce da su): “Ku riƙe abin da Muka ba ku da kyau, kuma ku tuna abin da yake cikinsa, don su zamo masu kiyaye dokokin Allah.”

172. Ka tuna kuma lokacin da Ubangijinka Ya fitar da zurriyar ’yan’adam daga tsatsonsu, Ya kuma sa su suka yi wa kansu shaida, (Ya ce da su): “Yanzu ba Ni ne Ubangijinku ba?” Suka ce: “E Kai ne, mun shaida.” Don kada a ranar alƙiyama ku ce: “Lalle mu mun kasance gafalallu a kan wannan.”

173. Ko kuma ku ce: “Iyayenmu da suka gabace mu kawai suka yi shirka, mu kuma zurriya ce da muka kasance a bayansu; yanzu Ka hallakar da mu saboda abin da maɓarnata suka yi?”

174. Kuma kamar haka ne Muke bayyana ayoyi, don su komo wa (gaskiya).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tuna wa Annabi (ﷺ) labarin Banu-Isra’ila lokacin da suka nemi Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kawo musu littafin da za su riƙa ƙarantawa suna aiki da shi. Lokacin da ya zo musu da littafin Attaura, wanda a ciki Allah ya yi alƙawura masu ƙarfi da su, to amma sai suka ƙi cika waɗannan alƙawura, suka bar aiki da koyarwar Attaura, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗaga dutsen Ɗuri-Sina a kansu yana reto kamar girgije yana yi musu inuwa, sai kuwa suka tabbatar cewa zai faɗo musu. Sai Allah ya ce musu, lalle su riƙe littafin Attaura da ya ba su da kyau, su yi aiki da hukunce-hukuncen da suke cikinsa don su tsare dokokinsa.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya tuna lokacin da ya fitar da zurriyyar ‘yan’adam daga tsatsonsu, ya sa suka yi wa kansu shaida da kansu, ya ce musu: “Yanzu ba ni ne Ubangijinku ba?” Suka amsa masa da cewa: “Kai ne, mun shaida.” Ya sa su sun yi wannan shaidar ne da kansu saboda gudun kada ranar alƙiyama su musanta faruwar hakan, su ce su ba su san cewa, Allah kaɗai ne ya cancanci a bauta masa ba, ko kuma su ce iyayensu ne suka fara yin shirka, su kuma ‘ya’ya ne da suka zo daga baya suka yi koyi da iyayensu a kan jahilci; don haka yaya Allah zai hallakar da su saboda iyayensu sun yi mummunan aiki sun bar Tauhidi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Yayin da Allah ya halicci Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya shafa bayansa, sai duk wani rai da Allah zai halicce shi daga cikin zurriyarsa har zuwa tashin alƙiyama ya fito daga tsatsonsa.” [Tirmizi #3076].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riƙe alƙawari daga tsatson Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a Na’amana (wato Arfa), ya fitar da duk wata zurriyya da zai halitta daga tsatsonsa, ya watsa su a gabansa kamar kiyashi, sannan ya yi magana da su baki da baki, ya ce: “Yanzu ba ni ne Ubangijinku ba?” Suka ce: “Kai ne Ubangijinmu, mun shaida.” Don kada ranar alƙiyama ku ce: “Haƙiƙa mu ba mu da masaniya game da wannan,” ko kuma ku ce: “Ai da ma can iyayenmu ne suka yi shirka mu kuma mun kasance zurriyya ne da muka biyo bayansu, yanzu ka kama mu da laifin da maɓarnata suka aikata?” [Ahmad #2455].

Abin nufi da wannan ayar shi ne, mutane tun suna tsatson Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ɗauki alƙawarin yin imani da Allah da kaɗaita shi wajen bauta, wannan ya sa duk wanda aka haifa daga cikinsu ake haihuwarsa a kan lafiyayyar halittarsa ta asali, to sai bayan sun girma ne sun mallaki hankalinsu Shaiɗan yake lalata musu ɗabi’arsu ta asali, ya kirawo su zuwa bautar wanin Allah da kafirce wa Allah da manzanninsa.
Sai Allah ya bayyana cewa, kamar yadda ya bayyana wannan ayar, haka yake bayyana sauran ayoyin Alƙur’ani don mutane su shiryu su dawo kan miƙaƙƙiyar hanya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ilimi shi kaɗai ba ya ɗaukaka mutum sai ya bi gaskiya ya yi aiki da ilimin da Allah ya ba shi.

2. Allah ya soki malamin da ba ya aiki da saninsa ta fuskoki daban-daban:
• Ya zaɓi ɓata bayan shiriya da kafirci bayan imani da gangan ba da rashin sani ba.
• Ya rabu da imaninsa gaba ɗaya, kamar yadda maciji yake saluɓewa ya rabu da saɓarsa gaba ɗaya.

• Shaiɗan ya bi shi kuma ya cim masa har ya farauce shi.
• Ya sani ya take saninsa kuma ya gurɓata aƙidarsa.
• Allah bai ɗaga matsayinsa da sanin da ya ba shi ba, wannan ya yi sanadiyyar halakarsa; da ma a ce bai san komai ba da sai ya fi masa alheri.
• Allah ya bayyana taɓarɓarewar lamarinsa da har ya yarda ya saki reshe ya kama ganye.
• Ya saki reshe ne ya kama ganye saboda tsananin sonsa da duniya da karkatarsa gare ta.
• Ya bar shiriyar da Allah ya yi masa, ya mayar da son zuciyarsa shi ne jagorarsa.
• Allah ya kwatanta shi da kare wanda yana daga cikin mafi ƙasƙancin dabbobi, mafiya rowa.
• Ya kamanta yadda wannan mutum yake matsanancin neman duniya ido rufe da wahalar da yake sha wajen tara ta, da kare wanda a kowane lokaci yake cikin lallage da zaro harshe.

3. Duk mutumin da ya zaɓi ya bi son zuciyarsa, ya biya sha'awarsa ta kowace hanya, to wannan ya ɓace daga kan hanyar samun jin daɗi na duniya da lahira.

4. Gwargwadon yawan ni'imar da Allah ya yi wa bawa, gwargwadon yadda zai yi nesa da Allah yayin da ya butulce masa.

5. Kada mutum ya ruɗu da ilimin da Allah ya ba shi; ya dai riƙa roƙon Allah kyakkyawan ƙarshe.

6. Ba da misalai yana da tasiri matuƙa wajen fito da gaskiya, yana da tasiri sosai wajen karɓar wa'azi.

7. Allah ne mai shiryarwa, shi ne kuma mai ɓatarwa, don haka bawa ya roƙe shi shiriya a koyaushe.

Suratul A'araf (175-178)

وَٱتۡلُ عَلَيۡهِمۡ نَبَأَ ٱلَّذِيٓ ءَاتَيۡنَٰهُ ءَايَٰتِنَا فَٱنسَلَخَ مِنۡهَا فَأَتۡبَعَهُ ٱلشَّيۡطَٰنُ فَكَانَ مِنَ ٱلۡغَاوِينَ ١٧٥ وَلَوۡ شِئۡنَا لَرَفَعۡنَٰهُ بِهَا وَلَٰكِنَّهُۥٓ أَخۡلَدَ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُۚ فَمَثَلُهُۥ كَمَثَلِ ٱلۡكَلۡبِ إِن تَحۡمِلۡ عَلَيۡهِ يَلۡهَثۡ أَوۡ تَتۡرُكۡهُ يَلۡهَثۚ ذَّٰلِكَ مَثَلُ ٱلۡقَوۡمِ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَاۚ فَٱقۡصُصِ ٱلۡقَصَصَ لَعَلَّهُمۡ يَتَفَكَّرُونَ ١٧٦ سَآءَ مَثَلًا ٱلۡقَوۡمُ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَأَنفُسَهُمۡ كَانُواْ يَظۡلِمُونَ ١٧٧ مَن يَهۡدِ ٱللَّهُ فَهُوَ ٱلۡمُهۡتَدِيۖ وَمَن يُضۡلِلۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ١٧٨

175. Ka kuma ƙaranta musu labarin wannan da Muka ba shi ayoyinmu, sai ya saluɓe (jikinsa) daga gare su, sai Shaiɗan ya bi shi, don haka ya kasance cikin halakakku.

176. Kuma da Mun ga dama da mun ɗaukaka shi a sanadiyyarsu, amma kuma shi ya karkata zuwa ga duniya, don haka ya biye wa son zuciyarsa. To misalinsa kamar misalin kare ne, idan ka kai masa ɗauki ya yi lallage, idan ma ka ƙyale shi zai yi lallage, wannan shi ne misalin waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu. Don haka ka ba da labari don su yi tunani.

177. Misalin waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu ya munana, kuma kawunansu suka kasance suna zalunta.

178. Wanda Allah Ya shiryar, to wannan shi ne shiryayye; wanda kuwa Ya ɓatar, to waɗannan su ne hasararru.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin wani mutum wanda Allah ya ba shi sanin hukunce-hukuncen shari'a, ya tumbatsa a ilimi wanda da a ce ya riƙe shi ya yi aiki da saninsa, to da

Allah ya ba shi ɗaukaka a duniya da lahira, to amma sai ya take wannan ilimi nasa, ya tuɓe rigar sanin da Allah ya sanya masa, Shaiɗan ya bi shi ya ɓatar da shi, ya hana shi aiki da iliminsa, ya koma duniya ce kaɗai abin nemansa. Allah ya kwatanta halinsa da halin kare wanda kowane lokaci harshensa a waje yake yana lallage yana haki; idan ya yi gudu ya gaji ya yi, idan ma ya tsaya ya huta ci gaba da zaro harshe yake yana lallagen. To kamar haka wannan mutumin ya zama; duniya ce kaɗai a gabansa, yana bin ta yana neman ta ido rufe, da zarar ya samu abin da yake hanƙoron samu, to zai sake yunƙurawa yana neman wani ne daban.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan shi ne misalin mutanen da suke ƙaryata ayoyinsa a kowane zamani kuma a kowane wuri.

Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ci gaba da faɗa wa mutanensa da Yahudawa irin waɗannan ƙissoshi don ko sa yi tunani.

Wannan misalin na mutanen da suka ƙaryata ayoyin Allah suka kuma zalunci kansu ya yi matuƙar muni. Wanda Allah ya shiryar da shi shi ne ya yi dace, wanda kuwa ya ɓatar da shi, to irinsu su ne suka yi hasarar duniya da ta lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan ɗan'adam ko aljan ya bar shiriyar Allah to ya fi dabba lalacewa da taɓarɓarewa.

2. Gafala tana daga cikin manyan abubuwa da suke hana bawa samun alherin duniya da na lahira.

3. Masu kira zuwa ga gaskiya ba za su taɓa yin shiru ba su ƙi faɗa wa mutane gaskiya ko su yi zamansu a gidajensu; ko da yaushe suna zama fitilu ne masu haska wa mutane hanyar tsira.

4. Kafiran aljannu 'yan wata ne.

5. An fara da ambaton aljannu sannan mutane saboda yadda mutane suke jin tsoron aljannu har wasu ma suke bauta musu.

6. Kyale kafirai suna ta kafircinsu, suna cin karensu ba babbaka, ba ya nufin abin da suke a kai gaskiya ne; Allah yakan yi musu talala ne har idan ya damƙe su, to babu mai iya kuɓutar da su.

7. Duk sunayen Allah sun kai matuƙa wajen kyau da ma'anoni na kamala. Don haka duk wani suna da babu kamala da matuƙar kyau tare da shi, to ba sunan Allah ba ne.

8. Da sunayen Allah ake roƙon sa ana tawassuli da su. Don haka bai dace a roƙi Allah da sunan wani ba Allah ba.

9. Allah shi ne kaɗai yake ba wa kansa suna, kuma ana sanin su ne ta hanyar wahayi, don haka ba ya halatta wani ya ƙirƙira masa wani suna daga wajensa.

Suratul A’araf (179-183)

وَلَقَدۡ ذَرَأۡنَا لِجَهَنَّمَ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِۖ لَهُمۡ قُلُوبٞ لَّا يَفۡقَهُونَ بِهَا وَلَهُمۡ أَعۡيُنٞ لَّا يُبۡصِرُونَ بِهَا وَلَهُمۡ ءَاذَانٞ لَّا يَسۡمَعُونَ بِهَآۚ أُوْلَٰٓئِكَ كَٱلۡأَنۡعَٰمِ بَلۡ هُمۡ أَضَلُّۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡغَٰفِلُونَ ١٧٩ وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَاۖ وَذَرُواْ ٱلَّذِينَ يُلۡحِدُونَ فِيٓ أَسۡمَٰٓئِهِۦۚ سَيُجۡزَوۡنَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٨٠ وَمِمَّنۡ خَلَقۡنَآ أُمَّةٞ يَهۡدُونَ بِٱلۡحَقِّ وَبِهِۦ يَعۡدِلُونَ ١٨١ وَٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا سَنَسۡتَدۡرِجُهُم مِّنۡ حَيۡثُ لَا يَعۡلَمُونَ ١٨٢ وَأُمۡلِي لَهُمۡۚ إِنَّ كَيۡدِي مَتِينٌ ١٨٣

179. Kuma lalle haƙiƙa Mun halitta wa Jahannama da yawa daga cikin aljannu da mutane; ga su da zukata da ba sa hankalta da su, ga kuma idanu da ba sa kallo da su, ga kunnuwa da ba sa sauraro da su. Waɗannan kamar dabbobi suke; a’a, sun ma fi (dabbobi) ɓacewa. Waɗannan su ne gafalallu.

180. Allah kuma Yana da sunaye mafiya kyau, don haka ku roƙe Shi da su; kuma ku rabu da waɗanda suke fanɗarewa game da sunayensa; da sannu za a yi musu sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa.

181. Kuma akwai wata al’umma daga cikin waɗanda Muka halitta suna shiryarwa da gaskiya, kuma da ita suke adalci.

182. Kuma waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, za Mu yi musu talala ta inda ba su sani ba.

183. Kuma Ina yi musu jinkiri ne; lalle kaidina mai ƙarfi ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, ya halicci mutane da aljannu masu yawa don wutar Jahannama, ya ba su zukata amma ba sa fahimtar gaskiya da su; ya ba su idanu amma ba sa ganin gaskiya da su; ya ba su kunnuwa amma ba sa sauraron maganar Allah su fahimta da su. Waɗannan halittu sun zamo kamar dabbobi ne waɗanda ba sa iya fahimtar komai. Kai sun ma fi dabbobi tabarɓarewa da lalacewa, saboda su dabbobi da ma can Allah bai yi musu tanadin hankali irin na mutum da aljan ba; don haka bai ɗora musu komai na ibada ba, saɓanin mutane da aljannu da Allah ya ba su isasshen hankali da za su bambance ƙarya da gaskiya da shi; to amma sai suka yi watsi da shi, suka ƙi amfani da shi yadda ya dace. Waɗannan sun tabbata su ne gafalallu ga ayoyin Allah da ambaton sa, masu watsi da abin da zai amfane su na imani da aiki na ƙwarai.
Sai kuma Allah ya bayyana cewa, yana da sunaye mafiya kyau waɗanda ya kira kansa da su a littafinsa ko Annabinsa ya kira shi da su a sunnarsa, sunaye masu ɗauke da siffofinsa mafi ɗaukaka na kamala, don haka ya umarci bayinsa su roƙe shi da su, su bar waɗanda suke fanɗarewa game da sunayensa, ko ta hanyar su raɗa wa wasu gumakansu sunayen Allah ko su ƙirƙira masa wasu sunayen daban ko su ƙi yarda da wasu. Allah ya ce zai saka musu da abin da suka kasance suna aikatawa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle Allah yana da wasu sunaye tis’in da tara, ɗari ba ɗaya, duk wanda ya kiyaye su to zai shiga Aljanna.” [Bukhari #2736, da Muslim #2677].

Sai kuma Allah ya bayyana cewa, a cikin mutanen da ya halitta ana samun al’ummar da take shiryuwa da gaskiya, take kuma shiryar da mutane zuwa gare ta, take kuma yi musu hukunci a tsakaninsu da adalci. Amma waɗanda suke jayayya da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), zai yi musu talala ne har lokacin da ya yi niyyar halaka su, kuma ya ninka musu azaba ta inda ba su sani ba; zai jinkirta musu ya ba su

tsawon rai don su ci gaba da kafircinsu da saɓon Allah. Lalle kuma kaidin Allah mai tsananin ƙarfi ne, duk wanda ya kama ba zai iya kuɓucewa ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a game da tunani da aiki da lura domin gano haƙiƙanin al'amura yadda suke.

2. Zurfafa tunani da ɗaukar izina shi yake kai mutum zuwa ga dacewa da ni'ima ta har abada.

3. Tunani a kan mutuwa da kusanto da ajali yakan sa mutum ya gaggauta tuba zuwa ga Allah, ya gyara ayyukansa.

4. Annabi (ﷺ) shi ne cikamakin annabawa da manzanni, don haka babu wani zance bayan Alƙur'ani da ya zo da shi da zai maye gurbinsa.

5. Shiriya da ɓata daga Allah ne.

Suratul A'araf (184-186)

أَوَلَمۡ يَتَفَكَّرُواْۗ مَا بِصَاحِبِهِم مِّن جِنَّةٍۚ إِنۡ هُوَ إِلَّا نَذِيرٞ مُّبِينٌ ١٨٤ أَوَلَمۡ يَنظُرُواْ فِي مَلَكُوتِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ وَأَنۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَدِ ٱقۡتَرَبَ أَجَلُهُمۡۖ فَبِأَيِّ حَدِيثِۭ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ ١٨٥ مَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَلَا هَادِيَ لَهُۥۚ وَيَذَرُهُمۡ فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ١٨٦

184. Shin ba za su yi tunani ba. Lalle abokin nasu fa babu hauka a tattare da shi. Ba kowa ne shi ba, face mai gargaɗi, mai bayyanarwa?

185. Shin ba za su yi duba cikin mulkin sammai da ƙasa da kuma abin da Allah Ya halitta ba, kuma lalle ya kusata a ce ajalinsu yana gab da zuwa, to da wane zance ne za su yi imani bayansa (wato Alƙur'ani)?

186. Wanda duk Allah Ya ɓatar, to ba shi da mai shiryar da shi. Kuma zai ƙyale su a cikin ƙetare iyakar da suke yi suna ɗimuwa.

Kafin aiko Manzon Allah (ﷺ) duk mutanen Makka da ya tashi a gabansu sun san shi mutum ne mai hankali, mai kyawawan halaye; ba a san shi da wani abu na rashin kyautawa ba, kowa yana son sa, yana yabon halayensa. Bayan da Allah ya ba shi manzanci, ya umarce shi da ya kirawo mutanensa ya faɗa musu gaskiya, ya hana su bautar gumaka, su bauta wa Allah shi kaɗai, sai kawai suka fara jifan sa da cewa, yana da taɓin hankali, alhali kuwa sun san ƙarya suke, ba su da wani dalili na yin haka sai hassada.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana jan hankalinsu cewa, me ya sa ba za su tsaya su yi tunani ba su gane cewa, Manzon Allah (ﷺ) ba shi da wani taɓin hankali, shi kawai mai gargaɗi ne gare su, kuma duk mai son gaskiya idan ya ji maganganunsa ya san gaskiya yake faɗa, babu mai guje masa sai mai ƙin gaskiya.
Hakanan su waɗannan masu ƙaryata saƙon da Annabi (ﷺ) ya zo da shi na Tauhidi, ashe ba za su tsaya su yi tunani game da mulkin sammai da ƙasa da duk wani abu da Allah ya halitta a cikinsu ba, su gane cewa, wanda ya yi wannan halittar kuma yake gudanar da ita shi kaɗai ne wanda ya cancanta a bauta masa? Hakanan su yi tunani game da ajalinsu mai yiwuwa ne ma ya matso kusa, don haka su gaggauta tuba zuwa ga Allah kafin mutuwarsu. To yanzu da wane irin zance ne za su yi imani bayan Alƙur'ani?

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya ɓatar to babu wanda ya isa ya shiryar da shi; yakan bar kafirai cikin shisshiginsu suna ta ɗimuwa su kasa gane hanyar gaskiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ga muminai su ji tsoron zuwan ranar alƙiyama, kuma hakan ya ƙara musu tsoron Allah don su kyautata ayyukansu, su guji aikata duk wani mummunan aiki.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɓoye sanin lokacin tashin alƙiyama don kowane mutum ya zama a shirye a kowane lokaci.

3. Duk wani hadisi da za a ambata cewa, wani zai san lokacin tashin alƙiyama, ko ya yi bayanin ƙididdigar shekarun da duniya za ta yi, wannan hadisin na ƙarya ne, bai halatta mumini ya gaskata shi ba, domin ya ci karo da ayoyin Alƙur'ani masu yawa.

4. Annabi (ﷺ) bai san gaibu ba sai abin da Allah ya sanar da shi, kuma bai mallaki amfanarwa ko cutarwa ga kansa ko ga wani ba, komai ka gani nufin Allah ne shi kaɗai.

Suratul A'araf (187-188)

يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلسَّاعَةِ أَيَّانَ مُرْسَىٰهَا ۖ قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ رَبِّى ۖ لَا يُجَلِّيهَا لِوَقْتِهَآ إِلَّا هُوَ ۚ ثَقُلَتْ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ لَا تَأْتِيكُمْ إِلَّا بَغْتَةً ۗ يَسْـَٔلُونَكَ كَأَنَّكَ حَفِىٌّ عَنْهَا ۖ قُلْ إِنَّمَا عِلْمُهَا عِندَ ٱللَّهِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٨٧﴾ قُل لَّآ أَمْلِكُ لِنَفْسِى نَفْعًا وَلَا ضَرًّا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُ ۚ وَلَوْ كُنتُ أَعْلَمُ ٱلْغَيْبَ لَٱسْتَكْثَرْتُ مِنَ ٱلْخَيْرِ وَمَا مَسَّنِىَ ٱلسُّوٓءُ ۚ إِنْ أَنَا۠ إِلَّا نَذِيرٌ وَبَشِيرٌ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿١٨٨﴾

187. Suna tambayar ka game da tashin alƙiyama yaushe ne matabbatarta take? Ka ce: "Sanin lokacinta yana wajen Ubangijina; ba mai bayyanar da lokacinta sai Shi. Ta yi nauyi a cikin sammai da ƙasa. Ba za ta zo muku ba sai katsahan." Suna tambayar ka kamar ka nace a kanta, ka ce: "Iliminta yana wajen Allah kaɗai, sai dai da yawa daga cikin mutane ba su sani ba.

188. Ka ce, "Ba na iya mallakar wa kaina wani amfani, ko wata cuta sai abin da Allah Ya ga dama. Kuma in da na kasance na san gaibu, lalle da na yawaita alheri, da kuma wani mummunan abu bai shafe ni ba. Ni ba wani ne ba face mai gargaɗi mai bushara ga mutanen da suke yin imani."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana wata mas'ala da kafirai suka matsa wa Annabi (ﷺ) tambaya a kanta domin wai su ƙure shi su bayyana ƙaryarsa a fili don kowa ya fahimta; ita ce batun tashin alƙiyama, wadda suka ce ba su yi imanin akwai ta ba. Sun yi ta tambayar Manzon Allah (ﷺ) cewa, in har maganar da yake faɗa ta cewa akwai ranar alƙiyama gaskiya ce, to yaushe ne za ta zo? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya faɗa musu cewa, sanin lokacinta yana wurin Allah, babu wanda ya isa ya bayyana lokacinta sai shi, hatta mala'iku da suke sammai da halittun da suke ƙasa ba wanda ya san lokacin zuwanta; za ta zo ba zato ba tsammani.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Annabi (ﷺ) yana zaune cikin jama'a sai Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo ya ce masa: "Yaushe ne lokacin tashin alƙiyama?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda aka tambaya bai fi mai tambayar sani ba." [Bukhari #50, da Muslim #9].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai sun tsananta game da tambayar Manzon Allah lokacin tashin alƙiyama kamar shi kansa ya tsananta tambaya ne game da ita har ya samu amsa. To ya faɗa musu cewa, shi ba shi da wata masaniya game da lokacin zuwanta, Allah ne kaɗai ya keɓanta da sanin hakan, sai dai mafi yawancin mutane ba sa sanin hakan.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Alƙiyama ba za ta tsaya ba har sai rana ta fito daga mafaɗarta, idan ta hudo mutane suka gan ta duk sai su ba da gaskiya, to a wannan lokacin ne, "Ba wani rai da imaninsa zai amfane shi idan a da can bai yi imani ba, ko bai aikata wani abu na alheri ba a cikin imaninsa." [*Suratul An'am*, aya ta 158]. Kuma lalle alƙiyama za ta tsaya a daidai lokacin da wasu mutane biyu za su baje hajarsu ta sayarwa a tsakaninsu, ba za su yi wannan cinikin ba kuma ba za su naɗe hajar ba. Kuma lalle alƙiyama za ta tsaya a daidai lokacin da mutum ya tatso nonon taguwarsa ya nufi gida, to amma ba zai samu damar ɗanɗanar sa ba. Kuma lalle alƙiyama za ta tsaya a lokacin da mutum yake gyara bakin tabkinsa, to amma ba zai sha ruwansa ba. Kuma lalle alƙiyama za ta tsaya lokacin da mutum zai ɗaga loma zuwa bakinsa, to amma ba zai samu damar ɗanɗanar ta ba." [Bukhari #6506, da Muslim #4954].

Sai kuma Allah ya umarci Annabi da ya faɗa musu cewa, shi ba zai iya mallaka wa kowa wani abu na amfani ba, kuma ba zai iya kare kansa daga wata cuta ba sai abin da Allah ya ga dama; idan da ya san gaibi kuwa to da ya aikata abubuwan da ya san za su haifar masa da amfani mai yawa, kuma da ya kauce wa duk wani sharri da yake ƙoƙarin samun sa. Allah ya umarce shi ya tabbatar musu da cewa, shi mai gargaɗi ne kawai, kuma mai albishir ga mutanen da suka yi imani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abin da ya sa ɗan'adam yake nutsuwa da matarsa shi ne, kasancewar daga jinsinsa na ɗan'adam take, don haka kowane jinsi ya fi karkata zuwa ga jinsinsa, ya fi samun ɗebe kewa a wajensa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa mutum ɗa nagari ba ƙaramar ni'ima ce ya yi masa ba, don haka wajibi ne a koyaushe ya riƙa gode wa Allah a kanta.

3. Duk wanda ba shi ne ya yi halitta ba, shi ma halittar sa aka yi, to bai dace da hankali a bauta masa ba. Allah ne kaɗai mahaliccin kowa da komai, don haka shi kaɗai ya wajaba a bauta masa.

Suratul A'araf (189-193)

۞هُوَ ٱلَّذِى خَلَقَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ وَجَعَلَ مِنْهَا زَوْجَهَا لِيَسْكُنَ إِلَيْهَا ۖ فَلَمَّا تَغَشَّىٰهَا حَمَلَتْ حَمْلًا خَفِيفًا فَمَرَّتْ بِهِۦ ۖ فَلَمَّآ أَثْقَلَت دَّعَوَا ٱللَّهَ رَبَّهُمَا لَئِنْ ءَاتَيْتَنَا صَٰلِحًا لَّنَكُونَنَّ مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿١٨٩﴾ فَلَمَّآ ءَاتَىٰهُمَا صَٰلِحًا جَعَلَا لَهُۥ شُرَكَآءَ فِيمَآ ءَاتَىٰهُمَا ۚ فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿١٩٠﴾ أَيُشْرِكُونَ مَا لَا يَخْلُقُ شَيْـًٔا وَهُمْ يُخْلَقُونَ ﴿١٩١﴾ وَلَا يَسْتَطِيعُونَ لَهُمْ نَصْرًا وَلَآ أَنفُسَهُمْ يَنصُرُونَ ﴿١٩٢﴾ وَإِن تَدْعُوهُمْ إِلَى ٱلْهُدَىٰ لَا يَتَّبِعُوكُمْ ۚ سَوَآءٌ عَلَيْكُمْ أَدَعَوْتُمُوهُمْ أَمْ أَنتُمْ صَٰمِتُونَ ﴿١٩٣﴾

189. Shi ne Wanda Ya halicce ku daga rai guda ɗaya, kuma Ya halicci matarsa daga gare shi, don ya sami nutsuwa tare da ita; to yayin da ya kusance ta, sai ta ɗauki yaron ciki, sai ta ci gaba (da harkokinta) da

shi, to yayin da (cikin) ya yi nauyi, sai suka roƙi Allah Ubangijinsu cewa: “Lalle idan Ka ba mu ɗa lafiyayye, lalle za mu kasance masu godiya.”

190. To yayin da Ya ba su ɗa lafiyayye, sai suka sanya masa abubuwan tarayya cikin abin da ya ba su. Allah kuwa ya ɗaukaka ga barin abin da suke shirka da Shi.

191. Shin sa riƙa haɗa (Allah) da abin da ba ya halittar komai, hasali ma su ne ake halitta?

192. Kuma ba za su iya taimaka musu ba, ba kuma za su iya taimaka wa kawunansu ba?

193. Kuma in da za ku kirawo su zuwa shiriya, to lalle ba za su bi ku ba. Duk ɗaya ne a gare ku kun kirawo su, ko kuma kun yi shiru?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, shi ne wanda ya halicci mutane daga rai guda ɗaya, wato Annabi Adam, sannan ya halitta masa matarsa Hauwa’u daga jinsinsa don ya samu nutsuwa da ita. To lokacin da ya sadu da ita sai ta ɗauki yaron ciki, ta ci gaba da harkokinta babu wata wahala, har lokacin da cikin ya tsufa ya yi mata nauyi, sai Annabi Adamu da matarsa Hauwa’u suka yi ta yin addu’ar Allah ya ba su lafiyayen ɗa kuma nagari; suka yi alƙawari idan har Allah ya karɓi addu’arsu ya biya musu buƙatarsu, za su gode masa da yin biyayya gare shi. To yayin da Allah ya karɓi addu’arsu ya ba su ɗa lafiyayye nagari, sai ‘ya’yansu ‘yan’adam suka sanya wa Allah abokan tarayya cikin ni’imar ‘ya’ya da arziƙi da ya ba su. Allah kuwa ya ɗaukaka game da abin da suke yin shirka da shi. Yanzu sa riƙa bauta wa wani abu tare da Allah wanda ba ya iya halittar komai, su ne ma ababen halitta, waɗanda wasu ne suka sassaƙa su ko suka gina su? Kuma ba za su iya taimakon masu bautar su da komai ba, ba za su iya kare su daga wani mummunan abu ba?
Idan da waɗannan mushirikai za su kirawo waɗannan gumakan nasu zuwa shiriya ba za su amsa musu ba, saboda sandararrun abubuwa ne ba sa ji ba sa magana ba su da hankali. Duk ɗaya ne a gare su ko su roƙe su ko su yi shiru, ba za su amsa musu ko su saurare su ba. To saboda za su riƙa bauta wa waɗanda haka siffarsutake?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wata halitta mai hankali da marar hankali bayin Allah ne.

2. Duk wani wanda mutum zai dogara da shi ba Allah ba yana roƙon sa kamar yadda yake roƙon Allah, to aikin banza yake yi, domin shi wannan da yake roƙo shi ma bawan Allah ne irinsa, ba zai iya tsinana wa kansa komai ba sai abin da Allah ya ga dama, balle kuma ya tsinana wa waninsa.

3. Duk wanda ya jiɓinci Allah da imani da aiki nagari, to shi ma Allah zai jiɓince shi da taimakonsa da kariyarsa.

Suratul A’araf (194-198)

إِنَّ ٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ عِبَادٌ أَمۡثَالُكُمۡۖ فَٱدۡعُوهُمۡ فَلۡيَسۡتَجِيبُواْ لَكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ١٩٤ أَلَهُمۡ أَرۡجُلٞ يَمۡشُونَ بِهَآ أَمۡ لَهُمۡ أَيۡدٖ يَبۡطِشُونَ بِهَآ أَمۡ لَهُمۡ أَعۡيُنٞ يُبۡصِرُونَ بِهَآ أَمۡ لَهُمۡ ءَاذَانٞ يَسۡمَعُونَ بِهَاۗ قُلِ ٱدۡعُواْ شُرَكَآءَكُمۡ ثُمَّ كِيدُونِ فَلَا تُنظِرُونِ١٩٥ إِنَّ وَلِيِّۦَ ٱللَّهُ ٱلَّذِي

نَزَّلَ ٱلۡكِتَٰبَۖ وَهُوَ يَتَوَلَّى ٱلصَّٰلِحِينَ ١٩٦ وَٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَسۡتَطِيعُونَ نَصۡرَكُمۡ وَلَآ أَنفُسَهُمۡ يَنصُرُونَ ١٩٧ وَإِن تَدۡعُوهُمۡ إِلَى ٱلۡهُدَىٰ لَا يَسۡمَعُواْۖ وَتَرَىٰهُمۡ يَنظُرُونَ إِلَيۡكَ وَهُمۡ لَا يُبۡصِرُونَ ١٩٨

194. Lalle waɗanda kuke kira ba Allah ba bayi ne kamarku, to ku kirawo su mana, sai su kuma su amsa muku idan kun kasance masu gaskiya ne.

195. Shin wai suna da ƙafafun da suke tafiya da su ne; ko suna da hannayen da suke damƙa da su, ko kuma suna da wasu idanuwa da suke gani da su; ko suna da wasu kunnuwa da suke saurare da su? Ka ce: “Ku kirawo abokan tarayyarku, sannan ku shirya mini makirci kuma kada ku saurara mini.”

196. “Lalle Majiɓincin lamarina Shi ne Allah Wanda Ya saukar da Littafi; kuma Shi Yake jiɓintar lamarin salihan bayi.”

197. Waɗanda kuke kira ba Shi ba kuwa, ba za su iya taimakon ku ba, kuma ba za su iya taimaka wa kawunansu ba.

198. Kuma idan da za ku yi kiran su zuwa ga shiriya, to fa ba za su ji ba; kuma za ka gan su suna kallon ka, alhali kuwa ba sa gani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙalubalantar mushirikai cewa, waɗanda suke bauta wa ba Allah ba su ma bayi ne kamarsu, in gaskiya ne su kirawo su su amsa musu a gani idan sun cancanci bauta.
Sai Allah ya tabbatar musu da kasawar waɗannan abubuwan bauta nasu, yana mai tambayar su, wai shin waɗannan gumakan nasu suna da ƙafafuwa da suke tafiya da su, ko kuwa suna da hannaye da suke kama abu da su su riƙe da ƙarfi waɗanda za su iya taimakon su da su, ko kuma suna da wasu idanuwa ne da suke gani da su, ko kuma suna da kunnuwa ne waɗanda suke ji da su? Idan sun tabbatar da cewa ba su da ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa, to ta yaya suke bautar su ba Allah ba?
Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa waɗannan mushirikai cewa, su kirawo gumakansu da suke bauta su haɗa ƙarfi da su don su cutar da shi, kada kuma su saurara masa in har sun isa, ko kuma cutarwa a hannunsu take. Sannan ya tabbatar musu cewa, mai taimakon sa wanda yake jiɓintar lamarinsa shi ne Allah wanda ya saukar da Alƙur’ani kuma yake jiɓintar lamarin duk mutane nagari, don haka shi ne mai ba shi kariya daga duk wani macuci azzalumi.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Mun fita wani yaƙi tare da Annabi (ﷺ) wajejen Najdu, sai lokacin barcin rana ya riske shi a wani kwazazzabo mai yawan itatuwa masu ƙaya, sai ya sami ƙarƙashin wata bishiya ya kwanta ya rataye takobinsa a jikinta, duk sauran sahabbai kowa ya tafi ya nemi inuwa ya kwanta. Muna tsakiyar hutawa sai muka ji Annabi (ﷺ) yana kiran mu, sai muka je inda yake, muna isa sai muka ga wani baƙauye, balarabe a gabansa zaune. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wannan mutum ya same ni ina barci, sai ya ɗauki takobina ya zare shi, sai na farka na gan shi tsaye a kaina yana riƙe da takobi a zare, sai ya ce: “Wane ne ya isa ya kare ka daga gare ni?” Sai na ce; “Allah ne.” Sai kawai ya mayar da takobi cikin kubensa ya zauna gabana. Ga shi nan zaune.” Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Sai Annabi ya ƙyale shi bai yi masa komai ba.” [Bukhari #4139, da Muslim #843].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa wa mushirikai cewa, gumakan da suke bauta wa ba Allah ba ba za su iya taimaka musu da komai ba, kamar yadda ba sa iya taimaka wa kansu; kuma

ko da za su kirawo su zuwa gaskiya ba jin su za su yi ba, za ka ga kamar suna kallon ka amma ba sa ganin komai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga Manzonsa (ﷺ) cewa: "Ka yi riƙo da afuwa, kuma ka yi umarni da abin da ya dace da shari'a, kuma ka rabu da jahilai," wannan aya ta tattaro duk wasu ɗabi'u na ƙwarai, ta ƙunshi kwaɗaitarwa bisa kyautata mu'amala da mutane da ba su haƙƙoƙinsu da Allah ya ce a ba su, da kau da kai daga duk wani rashin kyautawa nasu. Da mutane za su yi aiki da wannan ayar, to da ta ishe su zaman duniya, domin an umarci ɗan'adam da ya karɓi ɗan abin da ya sauwaƙa mai kyau daga mutane, kada ya nemi ƙari a wurinsu. Shi kuma haƙƙin da ya kamata ya ba su shi ne, ya yi musu umarni da kyakkyawan abu wanda shari'a ta yi umarni da shi, idan wani jahili kuma ya yi masa wauta, to ya kawar da kansa, ya yi afuwa kada ya ce sai ya ɗauki fansa ko ya ce zai rama wauta da wauta. To wace irin kamala kuma bawa zai samu da ta wuce wannan? Ko kuma wace irin siyasar zamantakewa da mutane ce ta kai wannan?

2. Babu abin da yake korar Shaiɗan daga bawa kamar ambaton Allah.

3. Masu tsoron Allah duk sa'adda Shaiɗan ya kai musu farmaki sukan mayar masa da martani ne da ambaton Allah da tuna girmansa, nan take sai waswasin Shaiɗan ya rabu da su, gaskiya ta ƙara bayyana a gare su. Wannan yana nuna cewa, duk wanda ya ci gaba da sakar wa Shaiɗan ragamarsa, to zai makantar da shi ne, ya toshe masa basira, ba zai taɓa ganin gaskiya ba ko ya fahimce ta idan ana faɗa masa ita.

4. Alƙur'ani ya ƙunshi duk wani dalili da bawa yake buƙatar ya sani game da Kaɗaitakar Allah ko gaskiyar Manzo da abin da ya zo da shi.

Suratul A'araf (199-203)

خُذِ ٱلۡعَفۡوَ وَأۡمُرۡ بِٱلۡعُرۡفِ وَأَعۡرِضۡ عَنِ ٱلۡجَٰهِلِينَ ١٩٩ وَإِمَّا يَنزَغَنَّكَ مِنَ ٱلشَّيۡطَٰنِ نَزۡغٞ فَٱسۡتَعِذۡ بِٱللَّهِۚ إِنَّهُۥ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ٢٠٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ إِذَا مَسَّهُمۡ طَٰٓئِفٞ مِّنَ ٱلشَّيۡطَٰنِ تَذَكَّرُواْ فَإِذَا هُم مُّبۡصِرُونَ ٢٠١ وَإِخۡوَٰنُهُمۡ يَمُدُّونَهُمۡ فِي ٱلۡغَيِّ ثُمَّ لَا يُقۡصِرُونَ ٢٠٢ وَإِذَا لَمۡ تَأۡتِهِم بِـَٔايَةٖ قَالُواْ لَوۡلَا ٱجۡتَبَيۡتَهَاۚ قُلۡ إِنَّمَآ أَتَّبِعُ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّ مِن رَّبِّيۚ هَٰذَا بَصَآئِرُ مِن رَّبِّكُمۡ وَهُدٗى وَرَحۡمَةٞ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٢٠٣

199. Ka yi riƙo da afuwa, kuma ka yi umarni da kyakkyawan abu, ka kuma kawar da kai daga wawaye.

200. Idan wani tunzuri daga Shaiɗan ya tunzura ka, to ka nemi tsarin Allah. Lalle Shi Mai ji ne, Masani.

201. Lalle waɗanda suka kiyaye dokokin Allah, idan wani Shaiɗan mai sa waswasi ya shafe su, sai su tuna (da Allah), sai ga su suna gani tar.

202. 'Yan'uwansu kuwa suna ƙara kawo musu ɗauki na ɓata, sannan su ba sa taƙaitawa.

203. Kuma idan ba ka kawo musu wata aya ba, sai su ce: "Don me ba ka ƙirƙiro ta ba?" Ka ce: "Ba abin da nake bi sai kawai abin da aka yi min wahayinsa daga Ubangijina. Waɗannan hujjoji ne daga Ubangijinku da kuma shiriya da kuma rahama ga mutanen da suke yin imani."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabinsa (ﷺ) da ya dinga yin afuwa gwargwadon hali daga halayen mutane, kada ya matsa musu, idan wani ya yi abin kirki daga cikinsu ya yaba masa, wanda kuwa ya yi rashin kyautawa ya yafe masa, ya haƙura da nasa haƙƙin, kuma ya yi umarni da abin da shari'a ta zo da shi, ya kawar da kai daga jahilai masu wauta. Ya kuma umarce shi idan wani waswasin Shaiɗan ya same shi, to ya nemi tsari daga Allah, haƙiƙa shi Allah mai ji ne masani.
Sai kuma ya bayyana cewa, mutane masu taƙawa, ta hanyar kiyaye dokokin Allah, idan Shaiɗan ya shafe su da wani waswasi ko fushi ko makamancin haka, nan da nan suke tuna Allah sai su dawo cikin hayyacinsu suna gani tar da zukatansu, don haka sai su yi watsi da waswasin Shaiɗan, su nisanci saɓon Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, kafirai da fajirai 'yan'uwansu shaiɗanu ne suke ƙawata musu hanyar ɓata, suke taimaka musu a kan saɓon Allah da kafirci, kuma su shaiɗanun ba sa gajiya ko ƙosawa da wannan mummunan aiki nasu suna nan tare da su ba dare ba rana.
Daga cikin irin ɓarnar da waɗannan shaiɗanu suke shukawa shi ne suna ingiza 'yan'uwansu kafirai suna damun Manzon Allah (ﷺ) da ya zo musu da mu'ujizoji waɗanda su suke buƙatar gani kafin su ba da gaskiya da shi; to idan bai zo musu da abin da suka nema ba, sai su ce, don me shi ba zai ƙago wannan mu'ujizar ba, idan har da gaske shi Manzon Allah ne? Sai Allah ya umarce shi da ya amsa musu da cewa, shi yana bin abin da aka yi masa wahayinsa ne kawai. Kuma wannan Alƙur'anin ya ƙunshi dalilai ne na sarari masu tabbatar da gaskiya da kuma shiriya da rahama ta duniya da lahira ga mutanen da suke yin imani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dole ne a yi shiru a daina surutu yayin ƙaratun Alƙur'ani.

2. Duk wanda ya yi kawaici ya saurari ƙaratun Alƙur'ani, to zai samu alheri mai yawa, kuma zai dace da rahamar Allah. Wanda kuwa ya ƙi yin shiru, to ya haramta wa kansa samun wannan rahamar.

3. Kwaɗaitarwa a kan yawaita ambaton Allah safe da yamma da nisantar shagala game da ambaton Allah.

4. Wajibi ne ga duk wanda zai ambaci Allah ya ambace shi cikin nutsuwa da ƙasƙantar da kai da guje wa ɗaga murya da ƙarfi.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba yana neman bayinsa su bauta masa ba ne don ya rasa masu bautar sa ko don wani amfani da zai samu daga masu bautar sa; Allah yana umartar su ne da su bauta masa domin su samu ninkin ladan abin da suka aikata; kuma ya ba su mafi kyan sakamako. Domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da bayinsa masu bautar sa tutur ba ƙaƙƙautawa dare da rana, wato mala'iku.

Suratul A'araf (204-206)

وَإِذَا قُرِئَ ٱلۡقُرۡءَانُ فَٱسۡتَمِعُواْ لَهُۥ وَأَنصِتُواْ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٢٠٤ وَٱذۡكُر رَّبَّكَ فِي نَفۡسِكَ تَضَرُّعًا وَخِيفَةً وَدُونَ ٱلۡجَهۡرِ مِنَ ٱلۡقَوۡلِ بِٱلۡغُدُوِّ
وَٱلۡأٓصَالِ وَلَا تَكُن مِّنَ ٱلۡغَٰفِلِينَ ٢٠٥ إِنَّ ٱلَّذِينَ عِندَ رَبِّكَ لَا يَسۡتَكۡبِرُونَ عَنۡ عِبَادَتِهِۦ وَيُسَبِّحُونَهُۥ وَلَهُۥ يَسۡجُدُونَ ٢٠٦

204. Kuma idan an ƙaranta Alƙur'ani, to ku saurare shi, ku kuma yi tsit, don a ji ƙan ku.

205. Kuma ka ambaci (sunan) Ubangijinka a ranka, kana mai ƙasƙantar da kai, kuma kana mai jin tsoro, ba kuma tare da ɗaga murya ba, safe da yamma, kada kuma ka zamo cikin gafalallu.

206. Lalle waɗanda suke wajen Ubangijinka, ba sa girman kai wajen bautar Sa, kuma suna tsarkake Shi, kuma gare Shi kawai suke yin sujjada.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar bayinsa da su saurara su kasa kunnuwa su yi tsit su daina hayaniya ko surutu lokacin da ake ƙaratun Alƙur'ani domin su sami rahamar Allah.
Ya kuma umarci Annabi (ﷺ) da ya yi ta ambaton sa a ransa da kuma harshensa, ta yadda wani ma ba zai san me yake faɗa ba, yana mai ƙasƙantar da kansa ga Allah, yana mai cike da tsoron sa da tsoron azabarsa. Kuma ya ambace shi da harshensa ba tare da ɗaga murya ba da safe da yamma, kar kuma ya zama daga cikin gafalallu.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Mun kasance tare da Manzon Allah (ﷺ) sai ya zamana duk sa'adda muka doso wani kwazazzabo sai mu yi ta hailala muna kabbara muna ɗaga muryarmu, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya ku mutane, ku sawwaƙa wa kawunanku, domin wanda kuke kira ba kurma ba ne, ba wanda ba ya tare da ku ba ne, lalle shi yana tare da ku kuma mai ji ne makusanci." [Bukhari #2993, da Muslim #2704].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya yi tsayuwar dare ya ƙaranta ayoyi goma, to ba za a rubuta shi cikin gafalallu ba; wanda kuma ya yi tsayuwar dare ya ƙaranta ayoyi ɗari, to za a rubuta shi a cikin masu ɗa'a (ga Allah), wanda kuma ya yi da ayoyi dubu, to za a rubuta shi cikin masu tsibi-tsibin lada." [Abu Dawud #1398].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mala'ikun da suke wurinsa ba sa girman kai ga bauta masa, kuma suna tsarkake shi daga duk wata tawaya ta hanyar yi masa tasbihi, sannan gare shi kaɗai suke yin sujjada.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ni ina ganin abin da ku ba kwa gani, ina kuma jin abin da ku ba kwa ji; sama ta yi ƙara kuma ya cancanta gare ta ta yi ƙarar, na rantse da wanda raina yake a hannunsa, a sama babu wurin shimfiɗa ʻyan yatsu huɗu, face akwai mala'ikan da ya sanya goshinsa yana mai sujjada ga Allah...." [Ahmad #21516, da Tirmizi #2312].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoron Allah shi ne linzamin jan zuciya. Da taƙawa ne kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake jan zukata zuwa ga gyara da sulhu tsakanin juna da kuma yi wa Allah da Manzonsa (ﷺ) ɗa'a.

2. Allah ya umarci muminai su yi sulhu da juna, su kawo ƙarshen duk wata rashin jituwa da ke tsakaninsu, su dasa bishiyar soyayya da ƙaunar juna a tsakaninsu, su kuma yafe wa juna.

3. Imani yana haifar wa mutum biyayya ga Allah da Manzonsa (ﷺ). Duk wanda ya bijire wa Allah da Manzonsa to wannan ba mumini ne ba. Wanda biyayyarsa ga Allah da Manzonsa ta ragu, to imaninsa ma ya ragu.

4. Mutum zai zama cikakken mumini ne idan ya lazimci aikata ayyuka nagari a koyaushe.

5. Ambaton Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne ambaton sunansa da tuna uƙubarsa da girmansa da kyakkyawan sakamakonsa da rahamarsa. To irin wannan zikirin ne yake haifar da raurawar zukata saboda tsoron Allah.

6. Imani yana ƙaruwa a zuciyar mumini ta hanyar ƙaratu da aiki da ayoyin Allah.

7. Imani yana ƙaruwa kuma yana raguwa. Malaman Sunna kamar Imamul Bukhari sun yi hujja da wannan ayar a kan ƙaruwar imani da hauhawarsa a zukatan muminai. Wannan ita ce aƙidar ɗaukacin magabatan wannan al'umma.

8. Ayyuka ba sa cika yadda ya kamata sai da dogaro ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

9. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa salla da zakka ya yabi mai kulawa da su, domin su ne kadarkon tsira.

10. Imani ba magana ce kawai da fatar baki ba, imani shi ne faɗa da cikawa.



8-Suratul Anfal

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:

Ana kiran ta da sunan *'Suratul Anfal'*, saboda an ambaci wannan lafazin a farkonta, kuma ba a sake ambatonsa a wani wuri ba a Alƙur'ani duka. *Al-Anfal* a wannan Sura yana nufin dukiyar ganima. An yi bayanin haukunce-hukuncen wannan dukiya a cikin wannan Sura.

An karƀo daga Sa'id ɗan Jubair, ya tambayi Abdullahi ɗan Abbas game da *Suratul Anfal* sai ya ce: "Ta sauka ne a Badar." [Bukhari #4545, da Muslim#3031].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:

Sura ce *Makiyya*, wasu malamai sun ambato ijma'i a kan haka. Maganar Ibn Abbas ta gabata a kan cewa an saukar da ita a Badar.

3. Jerin Saukarta:

Ita ce Sura ta tamanin da tara (89). Ta sauka bayan '*Suratu Ali-Imran*', gabanin '*Suratul Ahzab*'.

4. Adadin Ayoyinta:

A lissafin mutanen Makka da Madina da Basra ayoyinta sab'in da shida ne (76), a lissafin mutanen Sham kuwa adadinsu sab'in da bakwai ne (77). Amma a wurin mutanen Kufa ayoyinta saba'in da biyar ne (75).

5. Babban Jigonta:

• Bayanin dalilan samun nasara, da wasu daga cikin hukunce-hukuncen jihadi.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:

• Bayanin hukunce-hukuncen dukiyar ganima da umarni da taƙawa da bin Allah da Manzonsa cikin al'amarin wannan dukiya da waninta da umartar Musulmi da yin sulhu a tsakaninsu da kuma nuna cewa wannan yana daga cikin siffofin kamalar imani

• Siffofin muminai na gaskiya da yi musu albishir da samun manya-manyan matsayi a wurin Allah.

• Magana a kan fita yaƙin Badar da irin nasar da Allah ya ba wa muminai duk kuwa da cewa ba su fita cikin shiri ba.

• Kiraye-kiraye ga muminai don nuna musu abubuwan da aikata su alheri ne gare su duniya da lahira.

• Bayanin tsananin jahilcin mushirikai da taurin kansu.

• Bayanin darajar Manzon Allah (ﷺ) da nuna wa mushirikai cewa zamansa a Makka ba ƙaramar kariya ce gare su ba daga azabar Allah. Yana barin su kuwa sai azabar Allah ta same su saboda hana muminai isa ga Masallaci mai alfarma.

• Kira ga mushirikai a kan su daina nuna ƙiyayya ga Musulunci da cutar da Musulmi da kuma gargaɗin munafiƙai.

• Bayanin hukuncin dukiyar ganima daki-daki.

• Bayanin hukuncin ƙulla yarjejeniyar zaman lafiya tsakanin Musulmi da waɗanda ba Musulmi ba.

• Bayanin hukunce-hukuncen fursunonin yaƙi da hukuncin Musulmin da suka ƙi yin hijira zuwa Madina

Suratul Anfal (1-4)

يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْأَنفَالِ ۖ قُلِ ٱلْأَنفَالُ لِلَّهِ وَٱلرَّسُولِ ۖ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَصْلِحُوا۟ ذَاتَ بَيْنِكُمْ ۖ وَأَطِيعُوا۟ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١﴾ إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتْ قُلُوبُهُمْ وَإِذَا تُلِيَتْ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُهُۥ زَادَتْهُمْ إِيمَٰنًا وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ ﴿٢﴾ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ ﴿٣﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ حَقًّا ۚ لَّهُمْ دَرَجَٰتٌ عِندَ رَبِّهِمْ وَمَغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ ﴿٤﴾

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Suna tambayar ka game da ganimomi; ka ce (da su): “Ganimomi na Allah ne da kuma Manzo; saboda haka ku kiyaye dokokin Allah, ku kuma gyara tsakaninku, kuma ku bi Allah da Manzonsa, idan kun kasance muminai.”

2. Muminai na haƙiƙa (su ne) kaɗai waɗanda idan aka ambaci Allah, sai zukatansu su raurawa, idan kuma aka karanta musu ayoyinsa, sai su ƙara musu imani, kuma ga Ubangijinsu ne kawai suke dogara.

3. Waɗanda suke tsayar da salla kuma suke ciyarwa daga abin da muka arzurta su.

4. Waɗannan su ne muminai na haƙiƙa. Suna da muƙamai a wurin Ubangijinsu da kuma gafara da arziki na karamci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana buɗe wannan Surar ne da mayar da martani game da tambayar da sahabbai suke yi wa Annabi (ﷺ) dangane da hukuncin dukiyar ganima, musamman ganimar yaƙin Badar, wa ya kamata a ba wa? Kuma yaya za a raba ta? To shi ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi da ya faɗa musu cewa, ganima mallakinsa ce shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Manzonsa, watau shi Annabi (ﷺ) shi ne zai raba ya ba wa kowa kasonsa daga ciki. Don haka su ji tsoron Allah su kiyaye dokokinsa, su kuma sasanta tsakaninsu, kuma su bi Allah da Manzonsa, su yi aiki da umarninsa idan har su muminai ne da gaske.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffofin cikakkun muminai da cewa, su ne waɗanda idan sun ji an ambaci Allah sai zukatansu su girgiza don tsoron Allah; idan kuma aka karanta musu ayoyin Allah sai su ƙara musu imani da yaƙini, kuma ga Allah kaɗai suke dogara. Suna kuma masu tsayar da salla yadda ya kamata, sannan suna ciyar da dukiyarsu domin Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan su ne muminai na haƙiƙa, suna da darajoji maɗaukaka daga Ubangijinsu da gafara da arziki na karamci a Aljanna.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “A ranar yaƙin Badar, Manzon Allah (ﷺ) ya zaburar da sahabbansa a kan yaƙi, har ya yi alƙawarin duk wanda ya yi wani abin bajinta to yana da wani sakamako na musamman daga cikin ganima. To sai samarin cikinsu suka wuce gaba, dattawa kuwa suka tsaya a wajen tutoci ba su ƙara gaba ba. To lokacin da aka ci nasarar yaƙi sai dattawa suka ce wa samari, su ne suka riƙa ba su kariya ta baya, da a ce an koro su to da wurinsu za su dawo, don haka ba za su yarda samarin su su kaɗai su kwashe ganimar da aka samu ba. Su kuma samarin sai suka ƙi yarda suka ce Annabi (ﷺ) ne ya mallaka musu. Sai Allah ya saukar da waɗannan ayoyi.” [Dubi, Abu Dawud #2737, da Nasa’i, *As-Sunan Al-Kubra* #11133].

An karɓo daga Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Ayoyi huɗu sun sauka a kaina: Na samu wani takobi a wurin yaƙi, sai na zo da shi wurin Manzon Allah (ﷺ) na ce masa: “Ka ba ni shi a matsayin ganima.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Mayar da shi inda ka ɗauko shi.” Sai na kuma tashi na ce: “Ka ba ni shi a matsayin ganima ya Ma’aikin Allah?” Sai ya kuma cewa: “Ka mayar da shi.” Sai na kuma tashi na ce: “Ya Manzon Allah ka ba ni shi a matsayin ganima, za a bar ni hakanan ba ni da komai ne?” Sai Annabi (ﷺ) ya ce masa: “Mayar da shi inda ka ɗauke shi.” Sai wannan ayar ta sauka: (Suna tambayar ka game da ganima, ka ce: "Ganima ta Allah ce da Manzonsa").” [Dubi, Muslim #1748]. Wannan ayar ta farko, wasu malamai sun ce an shafe hukuncinta da aya ta 41 a cikin wannan Surar. Wasu kuma suka ce hukuncinta yana nan ba a shafe shi ba, suka ce, ma’anarta shi ne ganima duk ta Allah ce, domin duk abin da yake cikin duniya da lahira mulkin Allah ne. Shi kuma Annabi (ﷺ) shi yake da ikon bayanin yadda za a yi da wannan ganimar kamar yadda Allah ya sanar da shi a aya ta 41 cikin wannan Surar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matakan da Musulunci ya bi wajen tarbiyyar sahabban Manzon Allah (ﷺ) har ya zamana a kundin tarihin ɗan’adam kakaf ba a taɓa samun mabiya wani annabi kamarsu ba.

2. Ana tsayawa a yi jayayya ne lokacin da ya zamanto al’amura ba su bayyana a fili ba. Amma idan gaskiya ta fito fili to babu sauran wata jayayya kuma.

3. Duk ƙarfin maƙiya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba za su iya hana abin da Allah ya yi nufin zartarwa ba.

Suratul Anfal (5-8)

كَمَآ أَخۡرَجَكَ رَبُّكَ مِنۢ بَيۡتِكَ بِٱلۡحَقِّ وَإِنَّ فَرِيقٗا مِّنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ لَكَٰرِهُونَ ٥ يُجَٰدِلُونَكَ فِي ٱلۡحَقِّ بَعۡدَ مَا تَبَيَّنَ كَأَنَّمَا يُسَاقُونَ إِلَى ٱلۡمَوۡتِ وَهُمۡ يَنظُرُونَ ٦ وَإِذۡ يَعِدُكُمُ ٱللَّهُ إِحۡدَى ٱلطَّآئِفَتَيۡنِ أَنَّهَا لَكُمۡ وَتَوَدُّونَ أَنَّ غَيۡرَ ذَاتِ ٱلشَّوۡكَةِ تَكُونُ لَكُمۡ وَيُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُحِقَّ ٱلۡحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦ وَيَقۡطَعَ دَابِرَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧ لِيُحِقَّ ٱلۡحَقَّ وَيُبۡطِلَ ٱلۡبَٰطِلَ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٨

5. Kamar yadda Ubangijinka Ya fitar da kai daga gidanka (na Madina) da gaskiya, alhali lalle wata jama’a daga muminai tabbas suna ƙin (haka).

6. Suna jayayya da kai game da abin da yake tabbas, kai ka ce ana kora su ne wajen mutuwa, alhali kuwa suna kallo.

7. (Ka tuna) kuma lokacin da Allah Ya yi muku alƙawarin ɗayar jama’an nan guda biyu (na abokan gaba) cewa, lalle taku ce, sai kuka riƙa fatan marar wahalar ce za ta zama taku, alhali kuwa Allah Yana nufin Ya tabbatar da gaskiya da kalmominsa, Ya kuma tumɓuke tushen kafirai.

8. Don (kuma) Ya tabbatar da gaskiya, Ya kuma lalata ɓarna ko da kuwa kafirai sun ƙi (hakan).
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, kamar yadda wasu sahabbai ba su so yadda al’amarin rabon ganima ya kasance ba, to haka kuma lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fito da Annabi (ﷺ) daga gidansa domin haɗuwa da kafiran Kuraishawa, wasu muminai ba haka suka so ba, har ma suna jayayya da Annabi (ﷺ) a kan al’amarin gaskiya wanda Allah ya yi nufi, bayan ya bayyana a fili. Har sai da suka zama kamar ana jan su ne zuwa ga mutuwa saboda tsananin ƙinsu ga yaƙi.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jawo hankalin muminai yana cewa, su tuna lokacin da ya yi musu alƙawarin samun abu ɗaya daga cikin biyu, wato ko dai su yi nasarar rutsawa da kayan ayarin fatauci da Abu Sufyan yake jagoranci, ko kuma su haɗu da rundunar mayaƙan Makka. Amma su muminai a lokacin sun fi son su haɗu da ayarin fatauci na Abu Sufyan domin su ne ba sa ɗauke da makaman faɗa, kuma ba su da yawa. Shi kuma Allah ya riga ya yi nufin zai haɗa su ne da mayaƙan Kuraishawa, domin ya ba wa muminai nasara a kansu, ya bayyana rinjayen Musulunci a kan kafirci, ya kuma halakar da manya-manyan kafirai, ya bayyana izzar Musulmi da Musulunci, ya rushe kafirci da shirka ko da kuwa kafirai masu manyan laifuka ba sa son hakan.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya nemi agajin Ubangijinsa Allah, to zai amsa masa ya yaye masa damuwarsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi Annabi (ﷺ) da sahabbansa da cewa, sun koma gare shi lokacin da suke cikin damuwa, sun nemi taimakonsa shi kaɗai, sun dogara da shi, sun yi addu'a cike da ikhlasi. Wannan yana nuna girman matsayinsu a wurin Allah Ta'ala, musamman ganin yadda Allah ya amsa roƙonsu cikin gaggawa.

3. Wajibi ne a kan kowane Musulmi ya dogara ga Allah shi kaɗai, ya nemi agajinsa a kan duk wani abu da babu mai iya yin sa sai Allah. Don haka ba a neman agaji da annabawa ko waliyyai ko mala'iku a kan duk wani abu da Allah ne kaɗai mai yin sa, kamar bayar da lafiya ko arziki ko haihuwa da makamantansu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai ne mai ba da nasara. Don haka zuwan mala'iku ba shi ne ya ba wa sahabbai nasara ba, Allah ne ya ba su nasara ko da kuwa ta hanyarsu ne.

5. Samuwar gajeren barci ga sahabbai duk kuwa da halin da suke ciki na fuskantar abokan gaba waɗanda suka fi su yawa, yana nuna wannan barci ne na musamman daga Allah, domin idan mutum yana cikin tashin hankali ya samu ya yi barci komai ƙanƙantarsa, to zai samu sauƙi da nutsuwa. Ta wata fuskar kuma, Musulmi sun tsorata saboda ƙarancin adadinsu, ga kuma kafirai sun fi su yawa nesa ba kusa ba, kuma sun fi su shirin yaƙi da yawan makamai; bayan haka Musulmi suna cikin ƙishirwa mai tsanani. To ba don taimakon Allah da falalarsa ba, da har suka samu suka rintsa, suka samu hutu da kashe-gari ba za su sami ƙwarin gwiwar yaƙi ba balle nasara ta samu.

6. Bugu da ƙari kuma a ce barci ya ɗauke mutane da yawa lokaci guda wani al'amari ne da ya saba wa al'ada.

Suratul Anfal (9-11)

إِذْ تَسْتَغِيثُونَ رَبَّكُمْ فَٱسْتَجَابَ لَكُمْ أَنِّى مُمِدُّكُم بِأَلْفٍ مِّنَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ مُرْدِفِينَ ﴿٩﴾ وَمَا جَعَلَهُ ٱللَّهُ إِلَّا بُشْرَىٰ وَلِتَطْمَئِنَّ بِهِۦ قُلُوبُكُمْ ۚ وَمَا ٱلنَّصْرُ إِلَّا مِنْ عِندِ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿١٠﴾ إِذْ يُغَشِّيكُمُ ٱلنُّعَاسَ أَمَنَةً مِّنْهُ وَيُنَزِّلُ عَلَيْكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً لِّيُطَهِّرَكُم بِهِۦ وَيُذْهِبَ عَنكُمْ رِجْزَ ٱلشَّيْطَٰنِ وَلِيَرْبِطَ عَلَىٰ قُلُوبِكُمْ وَيُثَبِّتَ بِهِ ٱلْأَقْدَامَ ﴿١١﴾

9. Ku tuna lokacin da kuke neman taimakon Ubangijinku, sai Ya amsa muku cewa: "Ni zan kawo muku ɗauki na mala'iku dubu masu bibiyar juna."

10. Kuma (wannan taimakon) Allah bai sanya shi ba, sai don albishir a gare ku, don kuma zukatanku su nutsu da shi. Babu kuma wata nasara sai daga wurin Allah. Lalle Allah Mabuwayi ne Mai hikima.

11. (Ku kuma tuna) lokacin da gyangyaɗi yake kwashe ku (Allah) Yana Mai amintar da ku (daga tunanin abokan gaba), Ya kuma riƙa saukar da ruwa daga sama don Ya tsarkake ku da shi, Ya kuma tafiyar muku da waswasin shaiɗan, don kuma Ya ƙarfafa zukatanku Ya kuma tabbatar da dugaduganku da shi.

An karɓo daga Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “A ranar yaƙin Badar Annabi (ﷺ) ya kalli mushirikai ya ga yawansu ya kai dubu, ya kalli sahabbansa ya ga ba su fi mutum ɗari uku da sha tara ba, sai ya fuskanci alƙibla, ya ɗaga hunnayensa ya fara addu’a, yana cewa: “Ya Allah ka zartar mini alƙawarin da ka yi mini, ya Allah ka ba ni abin da ka yi mini alƙawari, ya Allah idan waɗannan jama’ar Musulmin suka halaka (a yau), to ba za a ci gaba da bauta maka a bayan ƙasa ba.” Bai gushe yana ta yin addu’a ba, ya ɗaga hannayensa sama, yana fuskantar alƙibla har sai da gwadonsa ya faɗi daga kafaɗunsa, Abubakar ya zo ya ɗauke shi ya mayar masa a kafaɗunsa, sannan ya rungumo shi ta bayansa, yana ce masa: “Ya Annabin Allah, addu’ar ta isa hakanan, lalle Allah zai cika maka alƙawarin da ya yi maka”. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyin.” [Muslim #1763].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa muminai cewa, su tuna lokacin da suka nemi taimako wajen Allah a kan ya ba su nasara bisa abokan gabarsu, sai ko Allah ya karɓi addu’arsu, ya yi musu alƙawarin zai taimaka musu da mala'iku har dubu waɗanda za su taho a jerin gwano don kawo musu ɗauki a yaƙin. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu wannan taimako ne don ya zama albishir na cin nasara a gare su, kuma zukatansu su ƙara natsuwa da zuwansu. Kuma nasara ba daga ko’ina take ba sai daga Allah, shi ne mabuwayi mai hikima.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “A wannan rana ta yaƙin Badar wani mutum Musulmi ya bi wani kafiri a guje, sai kawai ya ji ƙarar duka da bulala ta samansa, ya kuma ji wani sadauki yana cewa: “Gaba dai Haizum.” Sai ya ga wannan kafirin da ke gabansa ya faɗi rigingine, yana dubawa sai ya ga an datse hancin wannan mutumin an tsaga masa fuskarsa, kamar dukan bulala, ya kuma yi baƙi ƙirin. Sai wannan Musulmi mutumin Madina ya zo ya shaida wa Manzon Allah (ﷺ) abin da ya faru. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: “Ka faɗi gaskiya; wannan taimako ne daga sama ta uku.” A ranar Musulmi suka kashe kafirai saba’in, suka kama saba’in.” [Muslim #1763].

An karɓo daga Rifa’a ɗan Rafi’u (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Mala’ika Jibrilu ya zo wurin Annabi (ﷺ) ya ce masa: “Yaya kuke ganin waɗanda suka halarci yaƙin Badar daga cikinku?” Sai Annabi (ﷺ) ya ce masa: “Muna ganin su cikin mafiya falalar Musulmi.” Ko ya faɗa masa wata magana mai kama da haka. Sai Jibrilu ya ce: “Mu ma haka muke ganin mala’ikun da suka halarci yaƙin Badar daga cikinmu.” [Bukhari #3992].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nemi muminai su tuna lokacin da ya saka musu gyangyanɗi a idanunsu don su samu nutsuwar zukata, ya kuma saukar musu da ruwan sama don ya tsarkake su daga duk wani kari ko janaba, kuma ya kawar musu da waswasin Shaiɗan, kuma ya ƙarfafa zukatansu, ya kuma tabbatar musu da dugadugansu ta hanyar ruwan sama da ya sauka ya sa rairayin wurin ya yi ƙarfi, don haka ƙafafuwansu ko na dawakansu ba za su riƙa nutsewa a cikinsa ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin rahamar Allah ga bawansa ya sauƙaƙe masa hanyoyin bauta masa.

2. Bawa a koyaushe yana cikin matsananciyar buƙatar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafe shi ya ba shi jajircewa, idan kuwa bawa zai rabu da shi daidai da ƙiftawar idanu, to ya gama halaka.

3. Yana daga cikin sunnar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cewa duk sa'adda za a samu wata al'umma ta Musulmi da za su tsaya a kan hanyar Allah suna kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai da tsayar da dokokinsa a bayan ƙasa, sannan a samu wasu su fito don yin fito-na-fito da su tare da saɓa wa Allah da Manzonsa, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ba wa Musulmi jajircewa da ƙarfin gwiwa da nutsuwa har su cim ma nasara a kansu.

4. Wata babbar mu'ujiza ce ga Annabi (ﷺ) da kuma karama ga sahabbai Allah Ya saukar da mala'iku su taya su yaƙar kafirai a yaƙin Badar.

5. Saɓa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Manzonsa (ﷺ) yana daga cikin dalilan da suke jawo azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Anfal (12-14)

إِذْ يُوحِي رَبُّكَ إِلَى ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ أَنِّي مَعَكُمْ فَثَبِّتُواْ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْۚ سَأُلْقِي فِي قُلُوبِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلرُّعْبَ فَٱضْرِبُواْ فَوْقَ ٱلْأَعْنَاقِ وَٱضْرِبُواْ مِنْهُمْ كُلَّ بَنَانٍ ﴿١٢﴾ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ شَآقُّواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥۚ وَمَن يُشَاقِقِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَإِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿١٣﴾ ذَٰلِكُمْ فَذُوقُوهُ وَأَنَّ لِلْكَٰفِرِينَ عَذَابَ ٱلنَّارِ ﴿١٤﴾

12. (Ka kuma tuna) lokacin da Ubangijinka Yake wahayi zuwa ga mala'iku cewa: "Lalle Ni ina tare da ku, saboda haka ku ƙarfafa wa waɗanda suka yi imani gwiwa. Da sannu zan jefa tsoro cikin zukatan waɗanda suka kafirce, saboda haka ku doki wuyansu, kuma ku doki dukkanin gaɓoɓin hannaye da ƙafafu."

13.Wannan kuwa saboda sun saɓa wa Allah da Manzonsa. Duk wanda kuwa ya saɓa wa Allah da Manzonsa to lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne.

14. Wannan (uƙubar) sai ku ɗanɗane ta (a duniya), kuma ba shakka kafirai suna da azabar wuta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da Annabi (ﷺ) lokacin da ya yi wa mala'iku wahayi da cewa, lalle yana tare da su da taimakonsa da nasararsa, ya kuma umarce su cewa, su ƙarfafa wa muminai gwiwa, ya sanar da su cewa zai jefa tsoro da firgici a zukatan kafirai, don haka yana umartar muminai da su yi ta saran wuyoyin kafirai, da gaɓoɓin hannayensu da ƙafafuwansu. Wannan kuwa saboda sun saɓa wa Allah da Manzonsa suna kuma yaƙar su, kuma duk wanda zai aikata haka, Allah ba zai bar shi ba sai ya yi masa uƙuba da ta dace da shi, Allah kuma mai tsananin uƙuba ne. Ana kuma yi wa kafirai albishir da su ɗanɗani wannan azaba tun a nan duniya, kafin a je lahira su gamu da wata azabar mafi raɗaɗi da take jiran su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin gudu daga fagen yaƙi yayin da ake gwabzawa da abokan gaba.

2. Wanda duk ya gudu daga filin daga, to ya yi gudun gara ne ya faɗa gidan zago, domin ya jefa kansa ne cikin wutar Jahannama bai sani ba.

Suratul Anfal (15-16)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا لَقِيتُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ زَحۡفٗا فَلَا تُوَلُّوهُمُ ٱلۡأَدۡبَارَ ١٥ وَمَن يُوَلِّهِمۡ يَوۡمَئِذٖ دُبُرَهُۥٓ إِلَّا مُتَحَرِّفٗا لِّقِتَالٍ أَوۡ مُتَحَيِّزًا إِلَىٰ فِئَةٖ فَقَدۡ بَآءَ بِغَضَبٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَمَأۡوَىٰهُ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ١٦

15. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka haɗu da cincirindon waɗanda suka kafirta, to kada ku ba su baya.

16. Duk kuwa wanda ya ba su baya a wannan ranar idan dai ba wanda ya gudu da niyyar juyowa ya kai ɗauki ko kuma mai niyyar haɗuwa da wata jama'a (ta mayaƙa) ba, to haƙiƙa ya komo da fushin Allah, kuma makomarsa Jahannama ce; wannan makoma kuwa ta munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da cewa, idan sun haɗu da kafirai a filin yaƙi, suka kuma kusanci juna, to kada su kuskura su juya musu baya su gudu; lalle su tsaya su jajirce. Ya kuma yi gargaɗi mai tsanani ga duk wanda ya juya musu baya da cewa ya koma da fushin Allah, kuma makomarsa wutar Jahannama ce, tir kuwa da wannan makoma. To amma idan ya juya baya ne don yaudarar abokan gaba da niyyar zai sake kawo musu farmaki, ko kuma da niyyar ya koma ya haɗe da wata runduna ta Musulmi waɗanda zai dawo fagen fama tare da su ya taimaka a karya kafirai, to wannan babu komai ya halatta.

An karɓo daga Abu Hurairata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku nisanci abubuwa bakwai masu halakarwa." Sai sahabbai suka ce, waɗanne irin abubuwa ne? Sai ya ce, su ne: "Shirka da Allah da sihiri da kashe ran da Allah ya hana kashewa ba da wani laifi ba da cin dukiyar riba da cin dukiyar maraya da gudu daga fagen yaƙi da kuma yi wa muminai mata ƙazafi waɗanda ba su ji ba ba su gani ba." [Bukhari #2766, da Muslim #89].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani aiki na bawa ana jingina masa shi ne domin daga wajensa ya fito, amma Allah ne mai halittar aikin kuma shi ne mai sanya shi ya yi tasiri.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Annabi (ﷺ) cewa, ya yi jifa, amma ya kore masa tasirin wannan jifan, ya tabbatar da shi ga Allah shi kaɗai, domin wannan ya zama tarbiyyantarwa ce ga wannan al'umma, a nuna musu cewa, kada wani ya riƙa duban ayyukansa na ɗa'a, domin ga shi a nan Allah ya kore shi daga mafi cikar halittu, shi ne Annabi (ﷺ), don haka duk wanda ya yi wani aikin ɗa'a, to ya yi wa Allah godiya domin shi ne haƙiƙanin wanda ya huwace masa yin wannan aikin.

3. Yawa ba shi ke sa a ci nasara ba; haƙuri da jajircewa da dogaro ga Allah shi ne dalilin samun nasara a komai.

Suratul Anfal (17-19)

فَلَمۡ تَقۡتُلُوهُمۡ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ قَتَلَهُمۡۚ وَمَا رَمَيۡتَ إِذۡ رَمَيۡتَ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ رَمَىٰ وَلِيُبۡلِيَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ مِنۡهُ بَلَآءً حَسَنًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ١٧ ذَٰلِكُمۡ وَأَنَّ ٱللَّهَ مُوهِنُ كَيۡدِ ٱلۡكَٰفِرِينَ ١٨ إِن تَسۡتَفۡتِحُواْ فَقَدۡ جَآءَكُمُ ٱلۡفَتۡحُۖ وَإِن تَنتَهُواْ فَهُوَ خَيۡرٞ لَّكُمۡۖ وَإِن تَعُودُواْ نَعُدۡ وَلَن تُغۡنِيَ عَنكُمۡ فِئَتُكُمۡ شَيۡـٔٗا وَلَوۡ كَثُرَتۡ وَأَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٩

17. Saboda haka ba ku kuka kashe su ba, Allah ne Ya kashe su. Kuma ba ka jefa ba lokacin da ka jefa, sai dai Allah ne Ya jefa. Don kuma Ya jarrabi muminai da kyakkyawar jarrabawa. Lalle Allah Mai ji ne Masani.

18. Waccan (jarraba ku da aka yi gaskiya ne), kuma lalle Allah Mai raunana makircin kafirai ne.

19. Idan kuna neman zuwan hukunci ne (watau azaba), to haƙiƙa hukuncin ya zo muku. Idan kuka daina to shi ya fi muku alheri, idan kuma kuka koma, to za Mu koma, jama'arku kuma ba za ta amfana muku komai ba, komai yawanta kuwa, lalle kuma Allah Yana tare da muminai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, Annabi (ﷺ) da sahabbansa waɗanda suka halarci yaƙin Badar tare da shi ba su ne suka kashe kafiran da aka halaka a yaƙin ba; Allah ne ya kashe su, domin komai ya faru ne da taimakonsa da agajinsa. Shi ma Manzon Allah (ﷺ) da ya danƙi ƙasa da tafin hannunsa ya watsa ta a fuskokin kafirai ta kuma cika musu ido, to a haƙiƙa ba shi ne ya yi wannan jifan ba, Allah ne ya yi, kuma Allah ya yi haka ne don ya ni'imta muminai da kyakkyawan sakamako da za su yi masa godiya a kansa. Lalle Allah mai ji ne kuma masanin duk abin da yake faruwa.

An karɓo daga Hakim ɗan Hizam (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: "A ranar yaƙin Badar Manzon Allah (ﷺ) ya cika tafin hannunsa da tsakwankwani ya fuskanto mu, ya jefe mu da ita ya ce: "Fuskoki sun munana." Sai dukkanmu muka bazama a guje. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "Kuma ba ka yi jifa ba lokacin da ka yi jifa sai dai Allah ne ya yi jifan." [Ibn Jarir, *Tafsir* #15822; da Ibn Abi Hatim, *Tafsir*, #8906; da Ɗabarani, *Al-Mu'jamul Kabir* #3128].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu haka ne domin zai raunana duk wani makirci da ƙulli na kafirai da suke yi wa Musulunci da Musulmi.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana da mushirikai waɗanda suke yaƙar Annabi (ﷺ) da sahabbansa ranar yaƙin Badar, yana cewa, idan su ne suka roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya yi hukunci tsakaninsu da muminai, kuma ya saukar da uƙubarsa a kan azzalumai marasa gaskiya, to ga shi nan abin da suka roƙa ya tabbata, Allah ya taimaka wa wanda aka zalunta a kan azzalumi, ya tabbatar da gaskiyar mai gaskiya, sun ga abin da ya faru da su a ranar yaƙin Badar. Amma idan su kafirai sun bar kafircin da suke yi, to hakan shi ne ya fi zama alheri a gare su; idan kuwa suka sake komawa yaƙar Annabi (ﷺ) da sahabbansa, to tabbas Allah zai karya su; a kashe wasu a kama wasu daga cikinsu, kuma yawan adadinsu ba zai amfane su da komai ba, Allah kuma yana tare da muminai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mumini na haƙiƙa shi ne wanda zai ji umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Manzonsa ya yi musu ɗa'a.

2. Daga cikin mutane akwai wanda zai ji ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fahimce su sosai, amma sai ya yi watsi da aiki da su, ya ma riƙa fahimtar ba da shi ayoyin suke magana ba; da waɗansu ne daban,

ko da kuwa shi ya siffantu da abin da ayoyin suke hani a kai, to amma sai ya ce ana magana ne a kan kafirai ko munafukai, shi kuwa ba ɗaya ne daga cikinsu ba.

3. A wurin Allah gara dabbobi da kafirai, domin su ya ba su ji da gani da hankali don su yi amfani da su wajen yi masa biyayya amma sai suka ƙi, suka yi wa kansu hasara mai yawa.

4. Allah ba ya hana bawa samun wani alheri daga gare shi sai idan wannan bawan ya zamanto babu wani alheri a tare da shi.

Suratul Anfal (20-23)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَوَلَّوۡاْ عَنۡهُ وَأَنتُمۡ تَسۡمَعُونَ ٢٠ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ قَالُواْ سَمِعۡنَا وَهُمۡ لَا يَسۡمَعُونَ ٢١ ۞إِنَّ شَرَّ ٱلدَّوَآبِّ عِندَ ٱللَّهِ ٱلصُّمُّ ٱلۡبُكۡمُ ٱلَّذِينَ لَا يَعۡقِلُونَ ٢٢ وَلَوۡ عَلِمَ ٱللَّهُ فِيهِمۡ خَيۡرٗا لَّأَسۡمَعَهُمۡۖ وَلَوۡ أَسۡمَعَهُمۡ لَتَوَلَّواْ وَّهُم مُّعۡرِضُونَ ٢٣

20. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku bi Allah da Manzonsa kada kuma ku ba shi baya alhali kuwa kuna ji.

21. Kada kuma ku zama kamar waɗanda suka ce: “Mun ji,” alhalin kuwa su ba sa ji.

22. Lalle mafi sharrin masu tafiya a bayan ƙasa a wurin Allah (su ne) kurame (ga jin gaskiya) bebaye (ga faɗar gaskiya) waɗanda ba sa hankalta.

23. Da Allah Ya san da akwai wani alheri a tare da su, to da Ya jiyar da su (gaskiya); da kuma Ya jiyar da su ɗin ma, to da kuwa sun ba da baya suna masu bijirewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da su yi wa Allah da Manzonsa biyayya, kada su bijire musu alhalin suna jin abin da ake saukarwa na Alƙur’ani.Sai kuma ya yi musu kashedi da zama kamar mushirikai waɗanda idan sun ji an karanta littafin Allah sai su ce “mun ji”, to amma ba sa ɗaukar wani darasi daga abin da suka ji, suka zama kamar bebaye waɗanda ba sa jin komai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mafi sharrin masu tafiya a bayan ƙasa a wurin Allah su ne kafirai waɗanda suka zama kurame ba sa jin gaskiya, beyaye ba sa faɗar gaskiya, kuma ba sa hankaltar duk wani gargaɗi da Allah yake yi musu. Da kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san da akwai wani alheri a tare da su, to da ya ba su damar fahimtar ayoyin nasa; da kuma za a ƙaddara ya fahimtar da su ayoyin, to da sun bijire musu sun ƙi karɓar gaskiyar da ke cikinsu, saboda zukatansu sun riga sun gurɓace har ta kai babu wani alheri da zai shige su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rayuwa mai amfani tana samuwa ne ta hanyar amsa kiran Allah da Manzonsa (ﷺ). Duk wanda bai amsa wannan kiran ba, to rayuwarsa ba ta amfane shi ba; ta zama tamkar ta dabbobi.

2. Waɗanda suka amsa kiran Allah a fili da ɓoye su ne rayayyu na gaske; waɗanda ba su ba kuwa matattu ne ko da kuwa suna a raye.

3. Wanda ya fi kowa cikakkiyar rayuwa shi ne wanda ya fi kowa amsa kiran Allah da Manzonsa (ﷺ).

4. Idan ya zamanto abin da Manzon Allah (ﷺ) yake kira zuwa gare shi rayuwa ce, to duk wanda ya rasa wani ɓangare na sunnar Manzon Allah (ﷺ), to ya rasa wani ɓangare ne na rayuwarsa, don haka kowa yana samun rayuwa ne gwargwadon yadda ya amsa kiran Manzon Allah (ﷺ).

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da cikakken ikon ya kange tsakanin mutum da abin da zuciyarsa take so, domin komai a hannunsa yake. Wannan yana nuna girman muhimmancin tsoron Allah da gaggauta amsa kiran Allah da na Manzonsa (ﷺ).

6. Wajibi ne ga duk Musulmi ya tsawatar wa masu mummunan aiki, kowa daidai gwargwadon ikonsa, masu mulki su ne za su yi aiki da hannu; malamai da masu faɗa a ji su yi amfani da magana, sauran Musulmi kuma da ba sa iya komai su nuna ƙin abin a zuciya watau su ƙaurace wa masu mummunan aikin.

7. Idan ana aikata ɓarna, amma aka yi shiru aka ƙyale, to uƙubar Allah idan ta zo za ta shafi kowa da kowa ne, mai laifi da marar laifi.

8. Duk waɗanda suke cikin wani ƙunci, sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo musu sauƙi, to wajibi ne su yi wa Allah godiya a kan haka ta hanyar yi masa biyayya shi da Manzonsa (ﷺ).

Suratul Anfal (24-26)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱسْتَجِيبُواْ لِلَّهِ وَلِلرَّسُولِ إِذَا دَعَاكُمْ لِمَا يُحْيِيكُمْۖ وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ يَحُولُ بَيْنَ ٱلْمَرْءِ وَقَلْبِهِۦ وَأَنَّهُۥٓ إِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ٢٤
وَٱتَّقُواْ فِتْنَةً لَّا تُصِيبَنَّ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنكُمْ خَآصَّةًۖ وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ٢٥ وَٱذْكُرُوٓاْ إِذْ أَنتُمْ قَلِيلٌ مُّسْتَضْعَفُونَ فِى ٱلْأَرْضِ
تَخَافُونَ أَن يَتَخَطَّفَكُمُ ٱلنَّاسُ فَـَٔاوَىٰكُمْ وَأَيَّدَكُم بِنَصْرِهِۦ وَرَزَقَكُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَـٰتِ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ٢٦

24. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku amsa kiran Allah da na Manzo idan ya yi kiran ku ga abin da zai raya ku; kuma ku sani cewa, lalle Allah Yana kange tsakanin mutum da zuciyarsa, kuma lalle wurinsa ne za a tattara ku.

25. Ku kiyayi fitinar da ba kawai waɗanda suka yi zalunci za ta shafa ba, kuma ku sani cewa lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne.

26. Kuma ku tuna lokacin da kuke ‘yan tsirari masu rauni a bayan ƙasa, kuna tsoron kada wasu mutane su fauce ku, sai Ya tattara ku (a Madina) Ya kuma ƙarfafa ku da taimakonsa, Ya kuma arzuta ku da tsarkakan abubuwa don ku godiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da su amsa kiran Allah da Manzonsa, su kuma yi biyayya duk sa’adda Manzo ya kirawo su zuwa ga abin da zai amfane su a addininsu da rayuwarsu, duniyarsu da lahirarsu.

An karɓo daga Abu Sa’idu ɗan Al-Mu’alla (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kirawo ni sai ban amsa masa ba, sai na ce: “Ya Manzon Allah, ina salla ne a lokacin.” Sai ya ce: “Yanzu kai ba ka ji Allah ya ce ba: “Ya ku waɗanda suka yi imani, ku amsa kiran Allah da na Manzo idan ya kira ku ga abin da zai raya ku?” Sannan Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Zan koya maka Surar da ta fi kowace sura a Alƙur’ani girma kafin ka fita daga masallaci.” Sannan ya kama hannuna, yayin da na ga zai fita sai na ce masa: “Ba ka ce za ka koya min Surar da ta fi kowace sura girma a Alƙur’ani ba?” Sai ya ce: “Ita ce;

ita ce ayoyi bakwai da ake maimaitawa, kuma ita ce Alƙur'ani mai girma wanda aka ba ni." [Bukhari #4474].

Sai kuma Allah (ﷺ) ya sanar da bayinsa cewa, idan ya ga dama yana kange tsakanin mutum da zuciyarsa.

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) yana yawaita cewa: "Ya (Allah) mai jujjuya zuciya, ka tabbatar da zuciyata a kan addininka." Sai na ce: "Ya Annabin Allah, mun yi imani da kai da abin da ka zo da shi, shin kana jiye mana tsoro ne?" Sai ya ce: "Lalle zukata suna tsakankanin yatsu biyu daga 'yan yatsun Allah mai rahama yana juya su yadda ya ga dama." [Tirmizi #2140, da Ibn Maja #3834, da Ahmad #12107].

An karɓo daga Nawwas ɗan Sam'an (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Babu wata zuciya face tana tsakankanin 'yan yatsu biyu daga yatsun Allah mai rahama; idan ya ga dama ya miƙar da ita, idan kuma ya ga dama ya karkatar da ita." Ya kuma kasance yana cewa: "Ya mai jujjuya zukata, ka tabbatar da zukatanmu a kan addininka." [Ibn Maja #199, da Ahmad #17613].

Kuma zuwa gare shi za su koma a ranar alƙiyama.
Sai kuma Allah (ﷺ) ya umarce su su guji wani bala'i wanda idan ya zo ba zai tsaya a kan waɗanda suka jawo shi da zaluncinsu kaɗai ba; zai haɗo mai laifi da marar laifi gaba ɗaya, musamman waɗanda suka ga ana aikata ba daidai ba amma suka ƙi tsawatarwa tare da suna da iko a kan hakan. Kuma su sani cewa, Allah mai tsananin uƙuba ne.

An karɓo daga Zainab 'yar Jahshi (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Wata rana Annabi (ﷺ) ya tashi daga barci launin fuskarsa ya yi ja jawur yana cewa: "*La'ilaha illal Lahu! Larabawa* sun shiga uku saboda wani sharri da ya kusanto; a yau an buɗe ganuwar Yajuju da Majuju gwargwadon haka." Sai Sufyanu ya ƙulla cas'in ko ɗari da 'yan yatsunsa. Aka ce wa Annabi (ﷺ): "Yanzu za mu halaka alhalin a cikinmu akwai mutanen kirki?" Ya ce: "E, idan mutanen banza suka yi yawa." [Bukhari #7059, da Muslim #2880].

An karɓo daga Nu'umanu ɗan Bashir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Misalin wanda yake tsaye a kan iyakokin Allah da wanda ya auka cikinsu, kamar mutanen da suka yi ƙuri'a ne wajen shiga jirgin ruwa, wasu suka samu gidan sama wasu kuma gidan ƙasa, sai ya zamanto waɗanda suke gidan ƙasa idan za su ɗebi ruwa sai sun hau ɓangaren na saman jirgin. Sai suka yi shawarar cewa: 'Me zai hana mu fasa inda muke, ba sai mun dinga damun na samanmu ba?' To idan har su na saman suka ƙyale su suka aikata abin da suka yi niyya, to fa za su halaka ne gaba ɗayansu. Idan kuwa suka hana su to sai su tsira gaba ɗayansu." [Bukhari #2493].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su tuna lokacin da suke `yan kaɗan, maƙiyansu sun rena su, suna a tsorace kada kafirai su fauce su, su dinga kama su ɗaya bayan ɗaya suna kashe su, sai Allah ya tattaro su, ya sama musu wurin gudun hijira, wato Madina, ya ba su ƙarfi har suka ci nasara a kan abokan gabarsu, ya kuma arzuta su da abubuwan jin daɗi iri-iri don su yi wa Allah godiyar waɗannan ni'imomi da ya yi musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin cin amana komai ƙarancinta.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana jarrabar bayinsa da ni’imomin da ya ba su na dukiya da ‘ya’ya.

3. Jin daɗin lahira shi ne mafi girman jin daɗi wanda ba ya yankewa.

4. Tsoron Allah ga bawa shi ne alamar rabautarsa duniya da lahira.

5. Duk mai tsoron Allah, Allah zai ba shi damar bambance tsakanin gaskiya da ƙarya.

6. Tsoron Allah, wato kiyaye dokokinsa, ita ce hanyar kuɓuta daga duk wata damuwa ta duniya da ta lahira.
Suratul Anfal (27-29)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَخُونُواْ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ وَتَخُونُوٓاْ أَمَـٰنَـٰتِكُمۡ وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٢٧ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَآ أَمۡوَٰلُكُمۡ وَأَوۡلَـٰدُكُمۡ فِتۡنَةٞ وَأَنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥٓ أَجۡرٌ عَظِيمٞ ٢٨ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تَتَّقُواْ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّكُمۡ فُرۡقَانٗا وَيُكَفِّرۡ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۗ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٢٩

27. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ha’inci Allah da Manzo, (kada) kuma ku ha’inci amanoninku alhali kuna sane.

28. Kuma ku sani cewa, dukiyoyinku da ‘ya’yanku fitina ne, Allah kuma lalle a wurinsa lada mai girma yake.

29.Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka kiyaye dokokin Allah, to zai sanya muku (hanyar) tsira Ya kuma kankare muku munanan ayyukanku kuma Ya gafarta muku. Allah kuwa Ma’abocin babbar falala ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da su nesanci cin amanarsa da ta Manzonsa (ﷺ) da kuma duk wata amana da suka daƙa a tsakaninsu alhalin suna sane.
Amanar Allah ita ce bin dokokinsa ta hanyar aikata duk wani wajibi da barin duk wani abin da aka hana. Kiyaye amanar Manzon Allah (ﷺ) kuwa shi ne yi masa biyayya da girmama sunnarsa da aiki da ita.

An karɓo daga Abu Hurairata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah ya ce: “Alamomin munafuƙi uku ne: Idan ya yi magana sai ya yi ƙarya, idan kuma aka yi alƙawari da shi sai ya saba, kuma idan an amince da shi sai ya ci amana.” [Bukhari #33, da Muslim #59].

Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗakar da muminai cewa, dukiyarsu da ‘ya’yansu wata jarraba ce daga Allah gare su, domin ya ga shin za su bayar da haƙƙin Allah da ke cikinsu ko kuma son zuciya zai rufe musu ido su fifita son dukiyoyinsu da ‘ya’yansu a kan son Allah. Kuma ya kwaɗaitar da su cewa, duk wanda ya yi biyayya ga umarninsa yana da wani lada mai girma a wurinsa. Kuma idan har sun kiyaye dokokin Allah, sun bi umarninsa, sun guji haninsa, to zai sanya musu wata alama da za su bambance tsakanin ƙarya da gaskiya da ita, ya kuma sanya musu mafita daga duk wata damuwa ta duniya, ya ba su nasara, ya ƙarfafe su, kuma zai kankare musu laifukansu ya yafe musu. Allah kuwa ma’abocin babbar falala ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya azabtar da mai yin istigfari, domin istigfari yana shafe zunubi wanda shi ne yake jawo azabar Allah.

2. Ɗaukar kiɗa da tafi da waƙe-waƙe a matsayin addini hanya ce ta mushirikai.

3. Allah bai taɓa saukar wa wata al'umma azaba ba alhalin annabinsu yana cikinsu. Shi ya sa yayin da Manzon Allah (ﷺ) ya fita daga cikinsu ya yi hijira sai Allah ya saukar musu da azabar kisa ranar yaƙin Badar.

Suratul Anfal (30-35)

وَإِذْ يَمْكُرُ بِكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لِيُثْبِتُوكَ أَوْ يَقْتُلُوكَ أَوْ يُخْرِجُوكَۚ وَيَمْكُرُونَ وَيَمْكُرُ ٱللَّهُۖ وَٱللَّهُ خَيْرُ ٱلْمَٰكِرِينَ ﴿٣٠﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا قَالُواْ قَدْ سَمِعْنَا لَوْ نَشَآءُ لَقُلْنَا مِثْلَ هَٰذَآ إِنْ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٣١﴾ وَإِذْ قَالُواْ ٱللَّهُمَّ إِن كَانَ هَٰذَا هُوَ ٱلْحَقَّ مِنْ عِندِكَ فَأَمْطِرْ عَلَيْنَا حِجَارَةً مِّنَ ٱلسَّمَآءِ أَوِ ٱئْتِنَا بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٣٢﴾ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُعَذِّبَهُمْ وَأَنتَ فِيهِمْۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ مُعَذِّبَهُمْ وَهُمْ يَسْتَغْفِرُونَ ﴿٣٣﴾ وَمَا لَهُمْ أَلَّا يُعَذِّبَهُمُ ٱللَّهُ وَهُمْ يَصُدُّونَ عَنِ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ وَمَا كَانُوٓاْ أَوْلِيَآءَهُۥٓۚ إِنْ أَوْلِيَآؤُهُۥٓ إِلَّا ٱلْمُتَّقُونَ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٤﴾ وَمَا كَانَ صَلَاتُهُمْ عِندَ ٱلْبَيْتِ إِلَّا مُكَآءً وَتَصْدِيَةًۚ فَذُوقُواْ ٱلْعَذَابَ بِمَا كُنتُمْ تَكْفُرُونَ ﴿٣٥﴾

30. Kuma ka tuna lokacin da waɗanda suka kafirta suke ƙulla maka makirci don su tsare ka ko kuma su kashe ka ko su kore ka. Suna kuma shirya makirci Allah kuma Yana mayar musu sakamakon makircinsu. Allah kuma (Shi ne) Ya fi masu makirci iya (sakayyar) makirci.

31. Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu sai su ce: "Haƙiƙa mun ji, ai da mun ga dama ba shakka da mun faɗi irin wannan, wannan ba komai ba ne sai tatsuniyoyin mutanen da."

32. Ka tuna kuma lokacin da suka ce: "Ya Allah, idan wannan (Alƙur'ani) ya zamanto gaskiya ne daga wurinka yake, to sai Ka yi mana ruwan duwatsu daga sama ko kuma Ka kawo mana da wata azaba mai raɗaɗi."

33. Allah kuwa bai zamanto Mai yi musu azaba ba alhali kai kana cikinsu, kuma Allah ba zai yi musu azaba ba alhali suna neman gafara.

34. Me zai hana Allah Ya yi musu azaba alhali su suna hana mutane zuwa Masallaci mai alfarma, alhali kuwa ba su zamanto masu ƙaunar Sa na haƙiƙa ba. Masu ƙaunar Sa na haƙiƙa su ne masu taƙawa, sai dai yawancinsu ba sa sanin (haka).

35. Kuma sallarsu a Ɗakin (Ka'aba) ba ta zamanto ba sai fito da tafi. Sai ku ɗanɗani azaba saboda abin da kuka zamanto kuna yi na kafirci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin irin makirci da kafiran Kuraishawa suka shirya wa Annabi Muhammadu (ﷺ) lokacin da yake a Makka. Sun tattauna a tsakaninsu a *Darul-Nadwa*, sun shirya cewa, ko dai su tsare shi a wani wuri su hana shi fita har mutuwa, ko su kashe shi kowa ya huta, ko kuma su kore shi daga Makka ya tafi duk inda za shi. To amma daga ƙarshe ba su yi nasara ba. Allah ya sanar da Manzonsa (ﷺ) halin da ake ciki, kuma ya umarce shi ya yi hijira shi da sahabbansa.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wannan makirci nasu ne da yadda Allah ya kuɓutar da shi, su kuma Allah ya halakar da su, aka kashe yawancinsu a yaƙin Badar. Allah ne Fiyayyen mai mayar da makircin makirai a kansu, ya saka musu da abin da suka cancanta na sakamako.
Sai kuma ya bayyana cewa, idan ana karanta wa waɗannan kafirai ayoyin Alƙur'ani sai su dinga hura hanci suna cewa sun ji, ai idan da sun ga dama da su ma za su iya faɗar irinsa. Suka ƙara da cewa, ai wannan Alƙur'ani ba komai ba ne sai tatsuniyoyin mutanen farko.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) Ya tunatar da Manzonsa lokacin da kafiran Kuraishawa suke addu'ar cewa, idan har Alƙur'anin da Annabi (ﷺ) yake karantawa gaskiya ne, to Allah ya yi musu ruwan azaba na duwatsu daga sama, ko ya aiko musu wata azaba mai raɗaɗi.

An karɓo daga Anas ɗan Maliku (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Abu Jahlin ya ce: "Ya Allah, idan wannan (Alƙur'ani) ya zamanto gaskiya ne daga wurinka yake, sai ka yi mana ruwan duwatsu daga sama, ko kuma ka zo mana da wata azaba mai raɗaɗi." Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "(Allah kuwa bai zamanto mai yi musu azaba ba alhalin kai kana cikinsu. Kuma Allah ba zai yi musu azaba ba da a ce suna neman gafara. Me zai hana Allah ya yi musu azaba alhalin suna hana mutane zuwa Masallaci mai alfarma….)" [Bukhari #4649, da Muslim #2796].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa musu da cewa, ba zai yi musu azaba ba alhalin Annabi (ﷺ) yana cikinsu, kuma ba zai saukar musu da wata azaba ba da a ce suna neman gafararsa a kan kafircinsu da zunubbansu, sai dai ba sa neman gafarar. Allah ya bayyana cewa, me zai hana ya yi musu azaba alhalin suna hana Musulmi zuwa Masallaci mai alfarma, alhali su ba masoyansa ne ba, masoyansa na haƙiƙa su ne masu tsoron Allah ta hanyar kiyaye dokokinsa, sai dai yawancin mutane ba su san haka ba.Sai kuma ya bayyana cewa, sallar kafiran Kuraishawa a Ɗakin Ka'aba ba wani abu ne ba sai fito da tafi, don haka Allah ya ce, su ɗanɗani azaba saboda kafircinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A kowane zamani haka kafirai za su riƙa kashe maƙudan kuɗaɗe don su hana yaɗuwar Musulunci, domin su yaƙe shi su yaƙi Musulmi masu kira zuwa ga gaskiya. Amma duk da girman makircinsu da yawan dukiyar da suke fitarwa suna kashewa don yaƙi da addinin Allah, ba za su ci nasara ba, Musulunci zai ci gaba da yaɗuwa, su kuma za su ci gaba da nadama, sannan a lahira su gamu da matsananciyar azabar Allah.

2. Darasi ga Musulmi a nan shi ne su fahimci cewa, su ne ya fi cancanta su fitar da dukiyoyinsu su kashe su don ɗaukaka addinin Allah, domin su ne za su rabauta duniya da lahira idan sun yi hakan.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a nan ya ba da labarin abin da ba a yi ba, daga baya ya zo ya kasance, wato duk dukiyar da kafirai za su kashe ba za su yi nasarar murƙushe Musulunci da Musulmi ba, sai ga shi kuwa haka aka yi daga ƙarshe, Annabi (ﷺ) da sahabbansa su ne suka yi nasara, kafirai kuwa aka karya su, suka komo suna nadama.

Suratul Anfal (36-37)

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمۡ لِيَصُدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ فَسَيُنفِقُونَهَا ثُمَّ تَكُونُ عَلَيۡهِمۡ حَسۡرَةٗ ثُمَّ يُغۡلَبُونَۗ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِلَىٰ جَهَنَّمَ يُحۡشَرُونَ ٣٦ لِيَمِيزَ ٱللَّهُ ٱلۡخَبِيثَ مِنَ ٱلطَّيِّبِ وَيَجۡعَلَ ٱلۡخَبِيثَ بَعۡضَهُۥ عَلَىٰ بَعۡضٖ فَيَرۡكُمَهُۥ جَمِيعٗا فَيَجۡعَلَهُۥ فِي جَهَنَّمَۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٣٧

36. Lalle waɗanda suka kafirta suna kashe dukiyoyinsu don su toshe hanyar Allah. To da sannu za su kashe ta (dukiyar) sannan ta zama nadama a gare su, sannan kuma a rinjaye su. Waɗanda kuwa suka kafirta a Jahannama za a tattara su.

37. Don Allah Ya ware mummuna daga kyakkyawa, Ya kuma haɗa mummuna wani a kan wani, sannan Ya tattara shi gaba ɗaya cikin Jahannama. Waɗannan su ne asararru.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, kafirai suna ɓatar da dukiyoyinsu don su samu ƙarfin yaƙar Musulmi, su hana mutane shiga addinin Musulunci. To za su kashe dukiyoyin nasu, amma daga ƙarshe wannan zai zama nadama a gare su, domin za su gane cewa sun yi aikin banza wanda ba zai amfane su ba, a ƙarshe kuma a karya su, a yi galaba a kansu. Waɗanda suka kafirta kuwa Allah zai tattara su cikin wutar Jahannama ya azabtar da su a cikinta, domin ya rarrabe tsakanin muminai masu kyakkyawan hali da kafirai masu mummunan hali. Muminai su tafi Aljanna kafirai kuma su tafi wutar Jahannama. Allah ya tattara kafirai masu miyagun halaye a cikin wutar Jahannama wasu kan wasu. Waɗannan kafiran su ne suka yi hasara duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa, kasancewar kafirai sun kafe a kan kafircinsu da taurin kansu, amma bai hana Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da kiran su zuwa ga shiriya da yi musu tayin tuba da komawa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba.

2. Musulunci yana rushe duk laifukan da suka gabace shi.

3. Zindiƙi idan ya tuba ya bar zindiƙancinsa, to Allah zai karɓi tubansa.

4. Duk wani kafirin da ya tuba ya bar kafirci, to bai halatta a ci gaba da sukan sa da laifin da ya aikata a baya ba.

5. Idan kafirin da aka yaƙa ya musulunta, to ba za a kama shi da laifinsa na lokacin jahiliyya ba, ko da kuwa yana da alaƙa da haƙƙoƙin mutane.

6. Duk wanda yake ƙarƙashin tsaron Allah da kulawarsa, to babu abin da zai iya cutar da shi sai abin da Allah ya ga dama.

Suratul Anfal (38-40)

قُل لِّلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِن يَنتَهُواْ يُغۡفَرۡ لَهُم مَّا قَدۡ سَلَفَ وَإِن يَعُودُواْ فَقَدۡ مَضَتۡ سُنَّتُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٣٨ وَقَٰتِلُوهُمۡ حَتَّىٰ لَا تَكُونَ فِتۡنَةٞ وَيَكُونَ ٱلدِّينُ كُلُّهُۥ لِلَّهِۚ فَإِنِ ٱنتَهَوۡاْ فَإِنَّ ٱللَّهَ بِمَا يَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ٣٩ وَإِن تَوَلَّوۡاْ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَوۡلَىٰكُمۡۚ نِعۡمَ ٱلۡمَوۡلَىٰ وَنِعۡمَ ٱلنَّصِيرُ ٤٠

38. Ka ce da waɗanda suka kafirta idan suka daina, to za a gafarta musu abin da ya riga ya wuce, idan kuma suka koma to fa ba shakka al’adar mutanen farko ta gabata.

39. Kuma ku yaƙe su har sai ya zamanto ba wata fitina, addini kuma ya zamanto dukkaninsa na Allah. Sannan idan suka daina, to lalle Allah Mai ganin abin da suke aikatawa ne.

40. Idan kuma suka ba da baya, to ku sani cewa, Allah (Shi ne) Majiɓincin al’amarinku. Madalla da wannan Majiɓinci, kuma madalla da wannan Mai taimako.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) ya faɗa wa kafiran Kuraishawa cewa, idan sun bar kafircin da suke a kai, sun daina yaƙar Musulmi, to Allah zai gafarta musu zunubansu. Idan kuwa suka ci gaba, to sun ga dai abin da ya aikata gare su a ranar yaƙin Badar da kuma yadda ya hallaka al’ummomin da suka gabata waɗanda suka ƙaryata annabawansu.
Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai su yaƙi kafirai domin su kawar da shirka wadda za ta zama fitina ga mutane, kuma addini ya zamana na Allah ne tsantsa. Idan kuwa kafirai sun haɗu sun bar kafircin da suke yi da yaƙar muminai, to Allah yana ganin duk abin da suke aikatawa, kuma zai yi musu sakayya a kai. Idan kuwa sun bijire suka kafe a kan yaƙar muminai da kafircinsu, to Allah ya tabbatar wa muminai da su sakankance cewa, shi ne majiɓincinsu mai taimaka musu ya ba su nasara a kan waɗannan kafirai; madalla kuwa da mai taimakon masoyansa mai ba su nasara a kan maƙiyansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A farkon wannan Sura Allah ya karɓe duk wata dukiyar ganima daga hannun mayaƙan da suka yi fafutukar tara ta, ya daŋƙa ta ga kansa da Manzonsa (ﷺ) domin muminai su tsarkake zukatansu daga duk wata buƙata ta duniya, su yi jihadi don ɗaukaka kalmar Allah shi kaɗai. Sai kuma daga bisani Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dawo musu da ganimar bayan imani ya riga ya tabbata a zukatansu.

2. Ana raba dukiyar ganima kamar yadda Allah da Manzonsa (ﷺ) suka raba ta, watau kaso ɗaya bisa biyar na Allah ne da Manzonsa da dangin Annabi (ﷺ), su ne Banu Hashim da Banul Muɗɗalib da marayu da mabuƙata da kuma matafiyin da guzurinsa ya ƙare. Annabi (ﷺ) ko khalifansa shi ne zai riƙe wannan kason yana sarrafa shi ga waɗanda aka ambata. Sauran kashi huɗu kuwa na mayaƙa ne, za a raba musu, a ba mahayin doki kashi biyu; kashi ɗaya na dokinsa, kashi ɗaya kuma nasa; mai tafiya a ƙasa kuwa za a ba shi kashi ɗaya. Amma kashi ɗaya bisa biyar ɗin can za a kasa shi kashi biyar ne, kashi ɗaya na Allah ne da Manzonsa, za a yi amfani da shi a wajen maslaha ta Musulmai kowace iri ce ba tare da ƙayyadewa ba; kashi na biyu kuwa na dangin Annabi ne; kashi na uku na marayu ne; kashi na huɗu na mabuƙata ne, kashi na biyar na matafiyi ne.

Suratul Anfal (41-42)

*وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا غَنِمۡتُم مِّن شَيۡءٖ فَأَنَّ لِلَّهِ خُمُسَهُۥ وَلِلرَّسُولِ وَلِذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِ إِن كُنتُمۡ ءَامَنتُم بِٱللَّهِ وَمَآ أَنزَلۡنَا عَلَىٰ عَبۡدِنَا يَوۡمَ ٱلۡفُرۡقَانِ يَوۡمَ ٱلۡتَقَى ٱلۡجَمۡعَانِۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ٤١ إِذۡ أَنتُم بِٱلۡعُدۡوَةِ ٱلدُّنۡيَا وَهُم بِٱلۡعُدۡوَةِ ٱلۡقُصۡوَىٰ وَٱلرَّكۡبُ أَسۡفَلَ مِنكُمۡۚ وَلَوۡ تَوَاعَدتُّمۡ لَٱخۡتَلَفۡتُمۡ فِي ٱلۡمِيعَٰدِ وَلَٰكِن لِّيَقۡضِيَ ٱللَّهُ أَمۡرٗا كَانَ مَفۡعُولٗا لِّيَهۡلِكَ مَنۡ هَلَكَ عَنۢ بَيِّنَةٖ وَيَحۡيَىٰ مَنۡ حَيَّ عَنۢ بَيِّنَةٖۗ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَسَمِيعٌ عَلِيمٌ ٤٢

41. Kuma ku sani cewa duk abin da kuka samu na ganima to lalle ɗaya bisa biyar na Allah ne da Manzo da kuma makusantan (Annabi), da marayu da kuma miskinai da kuma matafiya, idan kun kasance kun yi imani da Allah da kuma abin da Muka saukar wa bawanmu ranar rabewa (ranar yaƙin Badar) ranar da ƙungiyoyin nan biyu suka haɗu. Allah kuwa Mai iko ne a kan komai.

42. Ku tuna lokacin da kuke a gacin da ya fi kusa (da Madina) su kuma suna gacin da ya fi nisa, ayarin (Abu Sufyan) kuwa yana ƙasa da ku. Da kuwa kun yi alƙawarin (haɗuwa a Badar) to babu shakka da kun saɓa wajen cika alƙawarin, sai dai kuma wannan ya faru ne saboda Allah Ya zartar da al'amarin da ya zamanto mai faruwa ne, don wanda ya hallaka ya hallaka da dalili, kuma wanda kuma ya rayu ya rayu da dalili. Lalle Allah Mai ji ne Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da muminai cewa, dukiyar da suka samu daga kafirai abokan faɗansu bayan sun yi nasara a kansu ganima ce a gare su. Yadda rabonta zai kasance kuwa shi ne, ɗaya bisa biyar na Allah ne da Manzonsa (ﷺ) da makusantansa, wato 'ya'yan Hashim da 'ya'yan Al-Muɗɗalib da marayu da miskinai da kuma matafiya masu buƙatar guziri, sauran kashi huɗu kuwa na mayaƙa ne. Wannan shi ne tanadin da Allah ya yi wa muminai idan har sun yi imani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da abin da ya saukar wa bawansa Annabi Muhammadu (ﷺ) na ayoyin Alƙur'ani, ranar da Allah ya rabe tsakanin ƙarya da gaskiya, wato ranar da rundunar Musulmi ta haɗu da rundunar kafirai a filin Badar. Allah mai iko ne a kan komai, don haka ya ba wa Musulmi nasara a kan kafirai duk da rashin yawansu, ya karya kafirai duk da tarin yawansu da tanadinsu.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Shaƙiƙu daga wani mutum daga ƙabilar *Banu Kaini ya* ce: "Na haɗu da Manzon Allah (ﷺ) a Wadil *Kura* yana taro wani doki sai na ce masa: "Ya Manzon Allah, me za ka ce a kan dukiyar ganima?" Sai ya ce: "Kaso ɗaya bisa biyar na Allah ne, kaso huɗun kuma na mayaƙa ne." Sai na ce: "Wani bai fi wani cancanta ba?" Sai ya ce: "E, ko da kibiyar da ɗayanku zai ka ciro ta daga kwarinta, shi bai fi ɗan'uwansa Musulmi cancantarta ba." [Abu Ya'ala #7179, At-Tahawi, *Sharhu Ma'anil* Athar #5198, Al-Baihaƙi, *As-Sunan Al-Kubra* #18012].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tuna wa muminai lokacin da suke filin Badar ta ɓangaren da ya fi kusa da Madina, su kuma kafirai suna ɓangaren da ya fi nisa da ita, su kuma ayarin da Abu Sufyan yake jagoranta mai ɗauke da kayan kasuwanci na Kuraishawa suna ƙasa da su, watau a gaɓar kwazazzabo. Allah ya nuna musu cewa, da a ce alƙawari ne su Musulmi suka yi da mushirikai a kan za su haɗu a filin Badar, to da sun saɓa wajen cika alƙawarin. Sai dai Allah ya riga ya shirya wannan haɗuwa don ya zartar da al'amarin da ya riga ya ƙaddara sai ya faru, don mai hallaka ya hallaka ta hanyar ci gaba da kafiricinsa bayan tsayuwar hujja a kansa, sannan wanda zai yi imani ya yi imani bayan hujja ta bayyana gare shi. Kuma lalle Allah mai ji ne masanin komai, zai yi wa kowa sakayya a kan aikinsa mai kyau ko mummuna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mafarkin annabawa gaskiya ne. Don haka wannan mafarkin na Annabi ya tabbata gaskiya ne, fassararsa ma gaskiya ce, domin ma'anar wannan mafarkin nasa shi ne, Allah ya nuna wa duka ɓangarorin biyu a fili cewa, abokan fafatawarsa ba su da yawa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gudanar da ƙaddararsa a tsari na ''*sababi da musabbabi*'' da Allah ya ga dama da duk abin da ya nufi zartar da shi ta hanyar mafarkin Annabi (ﷺ) sai kawai ya halicce shi a zukata da ƙwaƙwalen duk ɓangarorin biyu, ya nuna ƙarancin duk ɓangarorin biyu a idanuwansu ba tare da wancan sababi ba, to amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya ƙaddara faruwar komai da sababi.

3. Makomar komai tana ga Allah, shi ne mai yin yadda ya so, yadda kuma ya yi nufi, domin babu abin da yake fita daga ikonsa da ganin damarsa.

Suratul Anfal (43-44)

إِذۡ يُرِيكَهُمُ ٱللَّهُ فِي مَنَامِكَ قَلِيلٗاۖ وَلَوۡ أَرَىٰكَهُمۡ كَثِيرٗا لَّفَشِلۡتُمۡ وَلَتَنَٰزَعۡتُمۡ فِي ٱلۡأَمۡرِ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ سَلَّمَۚ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٤٣ وَإِذۡ يُرِيكُمُوهُمۡ إِذِ ٱلۡتَقَيۡتُمۡ فِيٓ أَعۡيُنِكُمۡ قَلِيلٗا وَيُقَلِّلُكُمۡ فِيٓ أَعۡيُنِهِمۡ لِيَقۡضِيَ ٱللَّهُ أَمۡرٗا كَانَ مَفۡعُولٗاۗ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ ٤٤

43. Ka tuna lokacin da Allah Yake nuna maka su cikin baccinka suna ‘yan kaɗan; da kuwa Ya nuna maka su da yawa fal, to ba shakka da kun tsorata kuma lalle da kun yi jayayya a cikin al’amarin, sai dai kuma Allah Ya kiyaye. Lalle Shi Masanin abin da ke zukata ne.

44. Ku kuma tuna lokacin da Yake nuna muku su a yayin da kuka gamu suna ‘yan kaɗan a idanuwanku, Yake kuma ƙarantar da ku a idonsu, saboda Allah Ya hukunta al’amarin da yake mai afkuwa ne. Kuma wurin Allah ne ake mayar da duka al’amura.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana magana a kan mafarkin da Annabi (ﷺ) ya yi ne, inda Allah ya nuna masa adadin kafirai ‘yan kaɗan. Da safe sai ya faɗa wa sahabbansa abin da ya gani a mafarki, sai suka yi murna sosai, suka samu ƙarfin gwiwa, suka yi ta zumuɗin haɗuwa da abokan gabarsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma yake sanar da shi cewa, da ya nuna masa su suna da yawa a cikin barcinsa, sannan ya farka ya sanar da muminai abin da ya gani, to da sun tsorata, gwiwarsu kuma ta yi sanyi, sun yi jayayya game da al’amarin yaƙi da waɗannan kafirai, to amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kiyaye haka ba ta faru ba. Lalle Allah shi masanin abubuwan da ke cikin zukata ne na imani ko na kafirci ko waswasi.
To domin a tabbatar da abin da Annabi (ﷺ) ya gani a mafarki sai Allah ya nuna wa Musulmi yawan kafirai ‘yan kaɗan domin su sami ƙarfin gwiwar shiga yaƙin. Su kuma kafirai sai ya nuna musu adadin Musulmi ‘yan kaɗan domin su rena su, su zaci yaƙar su ba wani abin a zo a gani ne ba, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zartar da al’amarin da ya ƙaddara babu makawa sai ya auku na wannan yaƙin da nasarar da Musulmi suka samu da hallaka kafirai. Wurin Allah ne kaɗai kuwa ake mayar da dukkan al’amura, shi ne mai yin hukunci da adalci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tubalin ginin al’umma guda biyar waɗanda nasara ba ta samuwa sai da su, su ne:
• Jajircewa
• Yawan ambaton Allah
• Biyayya ga Allah da Manzonsa (ﷺ)
• Haɗin kai da kauce wa rarrabuwa da rigingimu a tsakanin juna• Haƙuri da juriya

A kan waɗannan tubala ne ake gina ganuwar samun nasara a kan abokan gaba. Idan an rasa su, to za a rasa samun nasara baki ɗaya. Idan sun haɗu gaba ɗayansu, to za su ƙarfafi junansu, su kuma yi babban tasiri wajen samun nasara.

2. Sahabban Annabi (ﷺ) sun haɗa duk waɗannan tubala, don haka suka yi nasara a kan manya-manyan al’ummomin zamaninsu, suka ci garuruwa da yawa da yaƙi. A yau raunin waɗannan abubuwa ne ya jefa al’ummar Musulmi cikin halin da take ciki na ƙaskanci da wulaƙanci da koma-baya a rayuwa.

3. Wajibi ne ga bawa ya zamanto mai ambaton Allah a kowane lokaci.

4. Duk rintsin da masoyi zai shiga ba zai taɓa mantawa da masoyinsa ba.

5. Ambaton Allah babban makami ne a fagen fama domin ta hanyarsa ne ake samun taimakon Ubangiji da nasararsa.

6. Duk waɗanda za su haɗu da abokan gabarsu a fagen yaƙi amma su ƙi jajircewa, su kuma ƙi ambaton Allah da yawa, to waɗannan ba za su rabauta ba.

7. Jihadi ba shi da wani amfani sai tare da riƙo da sauran ayyukan ɗa'a da yin biyayya ga Allah da Manzonsa.

8. Hani game da rarrabuwa da rigingimu da jayayya tsakanin Musulmi.

9. Yawan jayayya yana kawo rarrabuwar kai a tsakanin al'umma.

10. Haƙuri da juriya suna da falala babba a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Anfal (45-47)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا لَقِيتُمۡ فِئَةٗ فَٱثۡبُتُواْ وَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ كَثِيرٗا لَّعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٤٥ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ رِيحُكُمۡۖ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٤٦ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ خَرَجُواْ مِن دِيَٰرِهِم بَطَرٗا وَرِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ وَٱللَّهُ بِمَا يَعۡمَلُونَ مُحِيطٞ ٤٧

45. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka haɗu da wata ƙungiya (ta mayaƙa), to sai ku dage, ku kuma ambaci Allah da yawa, don ku rabauta.

46. Kuma ku bi Allah da Manzonsa, kada ku rarrabu sai ku zama matsorata kuma ƙarfinku ya tafi; ku kuma yi haƙuri. Lalle Allah Yana tare da masu haƙuri.

47. Kada kuma ku zama kamar waɗanda suka fito daga gidajensu don fariya da kuma nuna wa mutane (watau riya), suna kuma hana (mutane) bin hanyar Allah. Allah kuwa Mai kewaye abin da suke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da cewa, idan sun haɗu da kafirai abokan faɗansu, to su dage wajen yaƙar su, su kuma dimanci ambaton Allah domin su rabauta.

An karɓo daga Abu Hurairata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Kada ku riƙa fatan haɗuwa da abokanan gaba, to amma idan kun haɗu da su, to sai ku yi haƙuri." [Bukhari #3026, da Muslim #1741].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abu Aufa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) a wani yaƙi da aka fita ya tara sahabbai ya ce musu: "Ya ku mutane, kada ku riƙa fatan haɗuwa da abokan gaba, ku

roƙi Allah lafiya, to amma idan kun haɗu da su, to ku yi haƙuri, ku sani Aljanna tana ƙarƙashin inuwowin takubba.” [Bukhari #2965, da Muslim #2509].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su yi masa biyayya, su yi wa Manzonsa (ﷺ) biyayya, kada su yi saɓani a tsakaninsu sai su samu matsala, ƙarfinsu ya gushe, gwiwoyinsu su yi sanyi, domin Allah yana tare da masu haƙuri.
Ya kuma hana su su zamanto kamar kafiran Kuraishawa waɗanda suka baro gidajensu don kawai su yi yaƙi da gaskiya, kuma su riƙa yi wa mutane alfahari da yawansu, su hana su shiga addinin Musulunci. Allah kuma mai kewayewa ne game da duk abin da suke aikatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mummunan ƙuduri da mugun nufi duka zuga ce ta Shaiɗan da waswasinsa.

2. Yana daga cikin makircin Shaiɗan, ya jefa ɗan’adam cikin halaka, sannan ya nesanta kansa da shi, ya koma gefe guda yana yi masa dariya da izgili.

3. Aljannu na iya rikiɗa cikin kamanni iri-iri, ciki har da kamannin mutum.

4. Shaiɗanu suna matuƙar tsoron mala’iku, don haka idan suka gan su gudu suke yi.

5. Nasara na samuwa ne ta hanyar dogaro ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba da yawan adadi ko tsananin ƙarfi ba, Allah kuma mabuwayi ne babu mai samun galaba a kansa.

6. Duk wanda ya miƙa al’amarinsa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya yi imani da cewa zai taimake shi, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ba shi kariya, ya tsare shi daga duk wani sharri ko makirci.

Suratul Anfal (48-49)

وَإِذْ زَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ أَعْمَٰلَهُمْ وَقَالَ لَا غَالِبَ لَكُمُ ٱلْيَوْمَ مِنَ ٱلنَّاسِ وَإِنِّى جَارٌ لَّكُمْ ۖ فَلَمَّا تَرَٰٓءَتِ ٱلْفِئَتَانِ نَكَصَ عَلَىٰ عَقِبَيْهِ وَقَالَ إِنِّى بَرِىٓءٌ مِّنكُمْ إِنِّىٓ أَرَىٰ مَا لَا تَرَوْنَ إِنِّىٓ أَخَافُ ٱللَّهَ ۚ وَٱللَّهُ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿٤٨﴾ إِذْ يَقُولُ ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ غَرَّ هَٰٓؤُلَآءِ دِينُهُمْ ۗ وَمَن يَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٤٩﴾

48. Kuma ku tuna lokacin da Shaiɗan ya ƙawata musu ayyukansu, ya kuma ce: “Babu wasu mutane a yau da za su yi galaba a kanku, lalle kuma ni maƙocinku ne.” Saboda haka lokacin da ƙungiyoyin biyu suka haɗu sai ya tsere a guje, ya kuma ce: “Lalle ni ba ruwana da ku, lalle ni ina ganin abin da ku ba kwa gani, lalle ni ina tsoron Allah. Allah kuwa Mai tsananin azaba ne.”

49. Ka tuna lokacin da munafuƙai da kuma waɗanda suke da rauni a zukatansu suke cewa: “Waɗannan addininsu ne ya ruɗe su.” Duk wanda ya dogara ga Allah kuwa to lalle Allah Mabuwayi ne Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) ya tuna lokacin da Shaiɗan ya ƙawata wa kafiran Kuraishawa miyagun ayyukansu, ya nuna musu cewa, a yau babu mai yin galaba a kansu, kuma shi mai ba su kariya ne. To amma lokacin da ƙungiyar Musulmi suka haɗu da ta kafirai, suka yi arba da juna, sai Shaiɗan ya dawo yana faɗa wa kafirai cewa, shi ba ruwansa da su domin ya ga abin da ya fi ƙarfinsa, shi yana jin tsoron Allah. Allah kuwa mai tsananin uƙuba ne.

An karƀo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “A ranar yaƙin Badar Iblis ya zo cikin rundunar shaiɗanu yana ɗauke da tutarsa ta yaƙi. Shaiɗan ya zo a kamannin wani mutum daga ƙabilar Banu Mudlij, wanda ake kira Suraƙatu ɗan Maliku ɗan Ju’shumin, ya ce wa mushirikai: “A yau babu wasu mutane da za su yi galaba a kanku, haƙiƙa kuma ni mai ba ku kariya ne.” Yayin da mutane suka ja daga, sai Manzon Allah (ﷺ) ya danƙi ƙasa a tafin hannunsa ya watsa a fuskokin mushirikai, sai suka juya da baya a guje. Sai Mala’ika Jibrilu ya nufi Iblisu lokacin yana riƙe da hannun wani mutum mushiriki, yana ganin Mala’ika Jibrilu sai ya fincike hannunsa ya juya baya a guje shi da jama’arsa, sai wani mutum ya ce masa: ‘Ya kai Suraƙatu, ba kai ne kake cewa za ka ba mu kariya ba?’ Sai ya ce: ‘Lalle ni ina ganin abin da ba kwa gani, haƙiƙa ni ina tsoron Allah. Allah kuwa mai tsananin uƙuba ne.’ Wato lokacin da Shaiɗan ya ga mala’iku.” [Ibn Jarir, *Al-Tafsir* #1683; da Ibn Abi Hatim, *At-Tafsir* Juzi’i na 5, Shafi na 1715].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar Annabi (ﷺ) ya tuna lokacin da munafuƙai masu cike da shakka a zukatansu suke cewa, addinin Musulmi ne ya ruɗe su har suka tarki yaƙar Kuraishawa alhalin sun fi su yawa da ƙarfi. To amma sun manta da cewa, duk wanda ya mayar da al’amari duka ga Allah, to lalle Allah mabuwayi ne mai hikima, babu abin da ya fi ƙarfinsa, kuma yana ajiye komai a muhallinsa da ya dace, yana karya duk wanda ya cancanci ya karya shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin uƙubobin saƀon Allah, cewa zunubbai suna kawar da ni’imar Allah daga bawa, su jawo masa azabarsa. Babu wata ni’ima da ta gushe ko wata azaba da ta sauka sai a sanadiyyar zunubi.

2. Tabbatar da adalcin Allah wajen mu’amalarsa ga bayinsa, duk wani abu da zai same su marar daɗi, to su ne suka jawo wa kawunansu.

3. Duk wata al’umma ko wani mutum ɗaya da yake son ya ga canji a rayuwarsa daga marar kyau zuwa mai kyau, ko marar daɗi zuwa mai daɗi, ko daga tsanani zuwa sauƙi, to makullan al’amarin suna hannunsu; shi ne kawai su canza aƙidunsu da halayensu da ayyukansu daga munana zuwa kyawawa, to za su ga kyakkyawan canji a rayuwarsu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mallaka wa ɗan’adam damar tsare ni’imomin da ya yi masa, har ma da haƀaka su idan ya ga dama, ta hanyar gode wa Allah, da gyara alaƙarsa da shi, to shi kuma zai ƙara masa.

5. Tabbatar da azabar barzahu, wadda take farawa daga lokacin zare rai daga jikin ɗan’adam.

Suratul Anfal (50-54)

وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذْ يَتَوَفَّى ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَضْرِبُونَ وُجُوهَهُمْ وَأَدْبَٰرَهُمْ وَذُوقُواْ عَذَابَ ٱلْحَرِيقِ ﴿٥٠﴾ ذَٰلِكَ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيكُمْ وَأَنَّ ٱللَّهَ
لَيْسَ بِظَلَّٰمٍ لِّلْعَبِيدِ ﴿٥١﴾ كَدَأْبِ ءَالِ فِرْعَوْنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۚ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ بِذُنُوبِهِمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِىٌّ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ﴿٥٢﴾
ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ لَمْ يَكُ مُغَيِّرًا نِّعْمَةً أَنْعَمَهَا عَلَىٰ قَوْمٍ حَتَّىٰ يُغَيِّرُواْ مَا بِأَنفُسِهِمْ وَأَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٥٣﴾ كَدَأْبِ ءَالِ فِرْعَوْنَ وَٱلَّذِينَ مِن
قَبْلِهِمْ ۚ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ فَأَهْلَكْنَٰهُم بِذُنُوبِهِمْ وَأَغْرَقْنَآ ءَالَ فِرْعَوْنَ ۚ وَكُلٌّ كَانُواْ ظَٰلِمِينَ ﴿٥٤﴾

50. Kuma da za ka ga lokacin da mala'iku suke ɗaukan ran waɗanda suka kafirta, suna dukan fuskokinsu da kuma bayansu, suna kuma (cewa da su): "Ku ɗanɗani azabar ƙuna."

51. "Wannan (ya faru gare ku ne) saboda abin da hannayenku suka aikata, kuma lalle Allah ba Mai zaluntar bayi ne ba."

52. (Al'adar kafiran Makka) kamar al'adar mutanen Fir'auna ce da kuma waɗanda suke gabaninsu. Sun kafirce wa ayoyin Allah, saboda haka Allah Ya kama su da zunubansu. Lalle Allah Mai ƙarfi ne, Mai tsananin uƙuba.

53. Wannan (kuwa) saboda Allah bai kasance Mai canza wata ni'ima da Ya yi wa wasu mutane ba har sai sun canja halayensu, lalle Allah kuma Mai ji ne Masani.

54. Kamar al'adar mutanen Fir'auna ce da kuma waɗanda suke gabaninsu. Sun ƙaryata ayoyin Ubangijinsu, sai Muka hallaka su saboda zunubansu, Muka kuma nutsar da mutanen Fir'auna (a cikin kogi). Dukkaninsu kuwa sun kasance azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, da a ce ya ga lokacin da mala'ikun mutuwa suke cizgar rayukan kafirai daga gangar jikinsu, suna dukan fuskokinsu da bayansu, to da ya ga wani babban abin tsoro; mala'iku suna yi musu gatse da cewa, su ɗanɗani azaba mai ƙuna saboda abin da suka aikata na kafirci da saɓon Allah. Kuma shi ba mai zaluntar bayinsa ba ne.
Ya zo cikin wani hadisi Kudusi Allah yana cewa: "Ya ku bayina, lalle ni na haramta wa kaina zalunci, kuma na sanya shi ya zamanto haramun a tsakaninku, don haka kada ku zalunci junanku...." [Muslim #2577].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, al'adar kafiran Kuraishawa dangane da kafircinsu ta yi kama da al'adar mutanen Fir'auna da sauran al'ummomin da suka ƙaryata ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a gabaninsu, kuma Allah ya hallaka su saboda kafircinsu da yawan saɓon Allah da suke yi. Lalle Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai ƙarfi ne kuma mai tsananin uƙuba, don haka ba wani kafiri da zai gagare shi.
Sai kuma ya bayyana cewa, ya hallakar da su ne saboda sun yi wa ni'imarsa butulci, sun kafirce masa bayan ya yi musu ni'ima, Allah kuwa ba ya canza ni'imar da ya yi wa wasu mutane har sai sun canza abin da ke tare da su, sun auka cikin kafirci da munanan ayyuka. Lalle Allah mai ji ne masanin komai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sake ambaton cewa, al'adar mushirikan Kuraishawa wajen ƙaryata gaskiya ta yi kama da al'adar mutanen Fir'auna a gabaninsu, waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah yayin da suka zo musu, sai Allah ya hallakar da su saboda zunubansu, ya kuma nutsar da mutanen Fir'auna a kogi. To duk waɗanda Allah ya halakar cikin kafiran farko da na Kuraishawa sun tabbata azzalumai ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Musulmi yana ɗaukan alƙawari ne don ya tsare shi, to amma idan yana jin tsoron a warware shi sai ya yi watsi da alƙawarin da ya ɗauka a sarari, don haka bai ci amana ba, bai kuma yi yaudara ba. Musulunci yana so ne ya ga mutane sun zama masu mutunci masu nagarta, ya kuma samar da nutsuwa a bainar jama'a. Don haka bai yarda a far wa mutanen da aka yi alƙawari da su ba bayan sun nutsu da alƙawarin da aka ɗaukar musu na zaman lafiya. Nagartar manufa ba ta bayar da dama mutum ya yi amfani da wata ƙazamar hanya don cim ma manufarsa ba, komai girman wannan manufa tasa kuwa.

2. Musulunci bai yarje wa 'ya'yansa cin amana ba, domin Allah ba ya son maciya amana.

3. Zamantowar addinin Musulunci shi ya fi kowane addini da ya gabace shi hujjoji bayyanannu waɗanda hankula kan yi saurin fahimtar su, shi ne dalilin da ya sa duk wanda ya ƙaryata hujjojin da Musulunci ya zo da su ya kasance mafi sharrin duk wata halitta mai tafiya a bayan ƙasa.

4. Idan aka riga aka yi yarjejeniyar zaman lafiya da kafiri, to haramun ne a yaudare shi ko a ci amanarsa, ko da kuwa shi ya kasance mai saurin cin amana ne ko mayaudari.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya dalilin jefar da alƙawarin zaman lafiya tsakanin Musulmai da abokan faɗansu shi ne cewa tsoron aukuwar ha'inci da yaudara daga gare su, bai nuna sai yaudarar ko ha'incin ya auku ba, domin al'amuran yaƙi da siyasar al'umma ana gina su ne a kan abubuwan da aka ga alamominsu sun fara bayyana, ba za a jira sai abin ya faru ba sannan a ɗauki mataki, domin idan shugabanni suka ɓata lokaci kafin ɗaukar wani mataki, to zai zamanto an jefa rayuwar al'umma cikin haɗari. Don haka ita siyasar al'umma ba daidai take da alƙalanci ba, wanda ba a yin hukunci a kan abin da bai faru ba sai ya faru, domin ko da an samu wani tsautsayi a nan to zai taƙaita ne a kan mutum ɗayan ko wasu 'yan tsirarun mutane kuma watakila za a iya shawo kan matsalar da wuri. Saɓanin idan matsala ta shafi dukkan al'umma ne, to al'amarinta yana da wuyar gyaruwa.

Suratul Anfal (55-59)

إِنَّ شَرَّ ٱلدَّوَآبِّ عِندَ ٱللَّهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ٥٥ ٱلَّذِينَ عَٰهَدتَّ مِنۡهُمۡ ثُمَّ يَنقُضُونَ عَهۡدَهُمۡ فِي كُلِّ مَرَّةٖ وَهُمۡ لَا يَتَّقُونَ ٥٦ فَإِمَّا تَثۡقَفَنَّهُمۡ فِي ٱلۡحَرۡبِ فَشَرِّدۡ بِهِم مَّنۡ خَلۡفَهُمۡ لَعَلَّهُمۡ يَذَّكَّرُونَ ٥٧ وَإِمَّا تَخَافَنَّ مِن قَوۡمٍ خِيَانَةٗ فَٱنۢبِذۡ إِلَيۡهِمۡ عَلَىٰ سَوَآءٍۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡخَآئِنِينَ ٥٨ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ سَبَقُوٓاْۚ إِنَّهُمۡ لَا يُعۡجِزُونَ ٥٩

55. Lalle mafi sharrin masu tafiya a bayan ƙasa a wurin Allah (su ne) waɗanda suka kafirta, don haka kuma su ba sa yin imani.

56. Waɗanda idan ka yi alƙawari da su sai su warware alƙawarinsu ko da yaushe, ba sa kuma kiyaye dokokin Allah (dangane da alƙawari).

57. Sannan idan ka haɗu da su a wurin yaƙi, to sai ka fatattaki na bayansu da su, don su (na bayan) sa wa'azantu.

58. Kuma idan kana jin tsoron wani ha'inci daga wasu mutane (da ka yi sulhu da su), to sai ka jefar musu shi (sulhun) a bayyane (ba da ha'inci ba). Lalle Allah ba Ya son masu ha'inci.

59. Kuma kada waɗanda suka kafirta su yi tsammanin sun tsere, lalle su ba za su gagari (Allah) ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, mafi sharrin halittun da suke tafiya a bayan ƙasa su ne waɗanda suka kafirta. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya san ba za su yi imani ba. Waɗanda Manzon Allah (ﷺ) ya yi alƙawarin zaman lafiya da su, to amma sai suke warware alƙawarin a lokuta da dama kuma ba sa kiyaye dokokin Allah wajen cika alƙawarin da suka ɗauka.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya yi wa kafirai uƙuba mai tsanani idan har ya haɗu da su a wurin yaƙi, ya fatattake su, don su zama wa'azi ga na bayansu.
Amma mutanen da ya yi yarjejeniya da su, sai kuma yake jin tsoron kada su yaudare shi su warware alƙawarin da suka ɗauka na zaman lafiya da Musulmi saboda irin take-takensu da za su bayyana, to Allah ya umarce shi da ya yi watsi da wannan alƙawarin na zaman lafiya, domin su duka ɓangarorin su san da

cewa, yanzu babu sauran alƙawarin zaman lafiya a tsakaninsu, don haka daga baya babu mai tuhumar Annabi (ﷺ) da cin amana, domin Allah ba ya son maciya amana.

An karɓo daga Sulaimu ɗan Amiru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “An yi yarjejeniyar zaman lafiya tsakanin Mu’awiya (Allah ya ƙara masa yarda) da Rumawa, sai ya zamanto yana ta yawo a cikin garuruwansu, har sai da lokacin yajejeniyar ya ƙare, sannan ya kai musu hari. Sai ya haɗu da wani mutum haye a kan dokinsa yana cewa: ‘Allahu Akbar! A cika alƙawari ban da yaudara.’ Da aka duba sai aka ga ashe Amiru ɗan Absatu ne. Sai Mu’awiya ya tambaye shi game da abin da yake faɗa, sai ya ce ya ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: ‘Duk wanda ya yi yarjejeniyar zaman lafiya da wasu mutane to kada ya warware alƙawari, kada kuma ya ɗaure shi tamau, ya bari har lokacin da aka ƙayyade ya ƙare, ko kuma ya jefar musu da alƙawarinsu a sarari.’ Sai Mu’awiya ya janye rundunarsa.” [Abu Dawud #2759, da Tirmizi #1580, da Ahmad #17015].

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Duk wani mayaudari yana da tutarsa a ranar alƙiyama, za a ɗaga masa ita gwargwadon yawan yaudararsa. Haƙiƙa babu mayaudarin da yaudararsa ta kai girman yaudarar shugaban jama’a.” [Muslim #1738].

Sai kuma Allah ya bayyana cewa, kada kafirai su taɓa tsammanin cewa sun kuɓuce wa Allah ba zai iya kama su ba; babu yadda za su yi su kuɓuce wa Allah ko su gagare shi domin shi mai cikakken iko ne a kan komai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Musulmi da su yi wa abokan gabansu kyakkyawan tanadi na makamai. Da ya ga dama da sai ya karya kafirai ba tare da muminai sun fuskance su da yaƙi ba, to amma Allah ya ƙaddara sai ya jarrabi bayinsa sashinsu da sashi, don haka ya umarce su da su yi tanadi kuma su yi haƙuri.

2. Tanadi domin jihadi na kayan faɗa irin su takubba da masu da kibau da koyon sukuwa a kan dawakai da iya harbi da duk abin da zai tsoratar da abokan gaba na makaman zamani na ƙasa da na sama da na ruwa da sauransu, farilla ce wadda idan wasu suka yi sun ɗauke wa sauran.

3. Tanadin ƙarfi da ɗaurarrun dawakai da Allah ya yi umarni da shi ya ƙunshi abin da a da mayaƙa suke buƙata a fagen yaƙi kamar takubba da masu da kibau da kwari da baka. A yanzu kuma ya ƙunshi tankokin yaƙi da bindigogi manya da ƙanana da roket-roket da jiragen sama da sauran duk abin da sojoji suke buƙata na kayan faɗa da kare kai na zamani.

4. Umarni da yin tanadi don jefa tsoro a zukatan magabta ya nuna ana yin tanadin ne don hana faruwar yaƙin ba don tayar da yaƙin ba. Wato kamar Allah yana cewa ne, ku yi kyakkyawan shiri don abokan gabanku su ji tsoron ku, don haka ba za su kawo muku hari ba, domin rauni shi ne yake ba wa mai ƙarfi ƙarfin gwiwar kawo hare-hare.

5. Umarnin Annabi (ﷺ) ya karkata ga sulhu idan abokan faɗansa sun karkato gare shi, yana nuna zaman lafiya aka fi so fiye da yaƙi.

6. Musulunci addini ne na zaman lafiya ba na yaƙi ba, sai dai ba zai taɓa yarda da wulaƙanci da cin zarafin ‘ya’yansa ba, shi ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su kare kansu tare da yaƙar zalunci idan aka hana su addininsu yadda Allah ya umarce su da shi.

7. Nasara ba ta samuwa ga al’umma sai an samu haɗin kai tsakanin ‘ya’yanta.

8. Duk mai gaskiya lalle ya nutsu, kada ya firgita ko ya tsorata saboda makircin masu makirci, domin Allah yana tare da shi, shi ne mai taimakon sa a koyaushe.

9. Yabo ga sahabban Annabi (ﷺ) da cewa, Allah ne ya haɗa tsakanin zukatansu da Musulunci ba da wani abin duniya ba.

10. Falalar Musulunci ga Larabawa. Annabi (ﷺ) ya same su kansu a rarrabe, kowacce ƙabila tana yaƙi da ‘yar’uwarta saboda wani abin da bai taka kara ya karya ba. Musulunci ya zo ya haɗa kansu; alaƙarsa ta fi alaƙar jini a wurinsa, har ya kasance mutum zai iya yaƙar mahaifinsa ko ɗan’uwansa a kan kare imaninsa. Sai ga shi Musulunci ya mayar da su tsintsiya maɗaurinki ɗaya.

Suratul Anfal (60-63)

وَأَعِدُّواْ لَهُم مَّا ٱسۡتَطَعۡتُم مِّن قُوَّةٖ وَمِن رِّبَاطِ ٱلۡخَيۡلِ تُرۡهِبُونَ بِهِۦ عَدُوَّ ٱللَّهِ وَعَدُوَّكُمۡ وَءَاخَرِينَ مِن دُونِهِمۡ لَا تَعۡلَمُونَهُمُ ٱللَّهُ يَعۡلَمُهُمۡۚ وَمَا تُنفِقُواْ مِن شَيۡءٖ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ يُوَفَّ إِلَيۡكُمۡ وَأَنتُمۡ لَا تُظۡلَمُونَ ٦٠ ۞وَإِن جَنَحُواْ لِلسَّلۡمِ فَٱجۡنَحۡ لَهَا وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٦١ وَإِن يُرِيدُوٓاْ أَن يَخۡدَعُوكَ فَإِنَّ حَسۡبَكَ ٱللَّهُۚ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَيَّدَكَ بِنَصۡرِهِۦ وَبِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٢ وَأَلَّفَ بَيۡنَ قُلُوبِهِمۡۚ لَوۡ أَنفَقۡتَ مَا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا مَّآ أَلَّفۡتَ بَيۡنَ قُلُوبِهِمۡ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ أَلَّفَ بَيۡنَهُمۡۚ إِنَّهُۥ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٦٣

60. Ku yi musu tanadin abin da kuke iyawa na ƙarfi da kuma tanadin ɗaurarrun dawakai, kuna tsorata maƙiya Allah kuma maƙiyanku da shi (tanadin), har kuma da wasu ban da su da ba ku san su ba, Allah ne kawai Ya san su. Kuma duk irin abin da kuka ciyar cikin hanyar Allah za a cika muku (ladanku) ba kuwa za a zalunce ku ba.

61. Idan kuma suka karkato ga sulhu, to sai kai ma ka karkato gare shi, ka kuma dogara ga Allah. Lalle Shi Mai ji ne Masani.

62. Idan kuma suka yi niyyar yaudarar ka, to lalle Allah Ya ishe ka. Shi ne wanda Ya ƙarfafe ka da taimakonsa da kuma muminai.

63. Ya kuma haɗa tsakanin zukatansu. Idan da za ka kashe duk abin da yake bayan ƙasa gaba ɗaya ba za ka iya haɗa tsakanin zukatansu ba, amma kuma Allah Ya haɗe tsakaninsu. Lalle Shi Mabuwayi ne Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da su yi wa maƙiyansu kafirai kyakkyawan tanadi na ƙarfin makamai da dawakan yaƙi don ɗaukaka addinin Allah. Waɗanda da su ne za su riƙa tsorata maƙiya Allah kuma maƙiyansu da ma wasu mutanen da su ba su san su ba, Allah ne kawai ya san su. Kuma ya bayyana musu cewa, dukiyoyinsu da suke kashewa saboda Allah, zai ba su cikakken ladansu a ranar alƙiyama ba tare da ya rage musu komai ba.

Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya karkata ga sulhu idan ya ga kafiran da suke yaƙar sa su ma sun karkato ga neman sulhu, ya kuma miƙa duk al'amuransa ga Allah; lalle Allah mai ji ne masanin komai.

Sannan ya sanar da shi cewa, idan kafiran suna neman sulhu ne da shi domin su yaudare shi, to Allah shi kaɗai ya ishe shi, kuma zai taimaka masa a kansu, kuma shi ne wanda ya ƙarfafe shi da nasararsa da kuma sahabbansa waɗanda suka yi imani da shi. Shi ya haɗa tsakanin zukatansu da Musulunci. Da a ce Manzon Allah (ﷺ) zai kashe duk dukiyar da take bayan ƙasa don ya haɗa tsakanin zukatansu da ba zai iya ba, to amma ga shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa tsakaninsu. Lalle shi mubuwayi ne mai hikima.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Zaidu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Yayin da Annabi (ﷺ) ya ci Hunainu da yaƙi, sai ya raba ganima, ya ba waɗanda ake lallashin zukatansu. Sai ya samu labarin su ma mutanen Madina suna son su samu nasu rabon na dukiyar ganima. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya tashi cikinsu ya yi musu huɗuba, ya gode wa Allah, ya kuma yabe shi, sannan ya ce: "Ya ku mutanen Madina, ashe ban same ku ɓatattu ba Allah ya shiryar da ku a sanadiyyata? Ban kuma same ku ba ku da komai ba, Allah ya wadatar da ku saboda ni? Ban same ku kawunanku a rarrabe ba, Allah ya haɗa kanku a dalilina?" Su kuma mutanen Madina suna amsa masa da cewa: Allah da Manzonsa su ne suka fi abin da za su goranta da shi. Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Ba za ku ba ni amsa ba?" Su kuma suna cewa: Allah da Manzonsa ne suka fi abin gorantawa. Sai ya ce: "Ai da kun ga dama sai ku ce kaza da kaza, abu kaza da kaza sun faru." Ya ambaci wasu abubuwa. "Sai kuma ya ce: "Shin ba za ku so idan mutane sun tafi da awaki da raƙuma ku kuma ku koma gidajenku da Manzon Allah ba? Mutanen Madina riga ce 'yar ciki, sauran mutane kuwa mayafi ne. Ba domin falalar hijira ba da na zaɓi in kasance ɗaya daga cikin mutanen Madina. Da a ce mutane za su bi wani kwazazzabo ko wata hanyar tsakanin duwatsu, da ni na bi kwazazzabon mutanen Madina da hanyarsu. Lalle ku a bayana za ku gamu da son kai, to ku yi haƙuri har ku haɗu da ni a Tabkina." [Bukhari #4330, da Muslim #1061].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa muminai alƙawarin zai ishe su da taimakonsa ya ba su rinjaye a kan maƙiyansu amma da sharaɗin su yi imani su bi Manzon Allah (ﷺ).

2. Kwaɗaitarwa a kan haƙuri da juriya.

3. Kafirai a wurin Allah ba komai ne ba, kuma muminai za su rinjaye su a fagen yaƙi komai yawansu, matuƙar su muminai sun siffantu da siffar imani da biyayya ga Manzon Allah (ﷺ).

4. Kafirci yana hana mutum ya fahimci abubuwa yadda suke, domin kafiri yakan yi watsi da duk kafofi na tunani da nazari da Allah ya ba shi, don haka sai ya kasa gane abin da zai amfane shi da wanda zai cutar da shi, saɓanin mumini.

5. Cewar kafirai mutane ne waɗanda ba sa fahimta yana nuna muhimmancin a fahimtar da sojojin Musulmi girman Allah da hukunce-hukuncen addininsu domin su yi yaƙi don Allah bisa basira da ilimi, su saɓa wa kafirai abokan gabarsu masu yaƙi cikin jahilci da rashin sanin Allah da addininsa.

6. Wajibi ne ga soja Musulmi ya tsaya a fagen daga kada ya gudu matuƙar abokan gaba ba su ninka su fiye da biyu ba.

Suratul Anfal (64-66)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ حَسۡبُكَ ٱللَّهُ وَمَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ حَرِّضِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ عَلَى ٱلۡقِتَالِۚ إِن يَكُن مِّنكُمۡ عِشۡرُونَ صَٰبِرُونَ يَغۡلِبُواْ مِاْئَتَيۡنِۚ وَإِن يَكُن مِّنكُم مِّاْئَةٞ يَغۡلِبُوٓاْ أَلۡفٗا مِّنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَفۡقَهُونَ ٦٥ ٱلۡـَٰٔنَ خَفَّفَ ٱللَّهُ عَنكُمۡ وَعَلِمَ أَنَّ فِيكُمۡ ضَعۡفٗاۚ فَإِن يَكُن مِّنكُم مِّاْئَةٞ صَابِرَةٞ يَغۡلِبُواْ مِاْئَتَيۡنِۚ وَإِن يَكُن مِّنكُمۡ أَلۡفٞ يَغۡلِبُوٓاْ أَلۡفَيۡنِ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٦٦

64. Ya kai wannan Annabi, Allah Ya ishe ka, kai da kuma muminai waɗanda suka bi ka.

65. Ya kai wannan Annabi, ka zaburar da muminai a kan yaƙi. Idan daga cikinku akwai (mutum) ashirin masu haƙuri to za su rinjayi (mutum) ɗari biyu (kafirai). Idan kuma daga cikinku akwai (mutum) ɗari to za su rinjayi (mutum) dubu daga waɗanda suka kafirta, saboda su mutane ne da ba sa ganewa.

66. Yanzu Allah Ya sassauta muku, Ya kuma san cewa a cikinku akwai raunana, saboda haka idan ya zamanto a cikinku akwai (mutum) ɗari masu haƙuri to za su rinjayi (mutum) ɗari biyu (kafirai). Idan kuma ya kasance akwai (mutum) dubu daga cikinku to za su rinjayi (kafirai) dubu biyu da izinin Allah. Allah kuma Yana tare da masu haƙuri.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tabbatar wa da Annabi (ﷺ) cewa, ya isar masa, kuma ya isar wa mabiyansa muminai, zai iya yi musu duk wani gatanci na al’amarin addini da rayuwa, kuma zai ba su nasara a kan maƙiyansu.Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya kwaɗaitar da muminai sosai a bisa yaƙi, su yi haƙuri a lokacin arangama da maƙiyansu, su dage sosai wajen yaƙar su. Idan aka samu mutane ashirin masu haƙuri daga cikinsu, to za su rinjayi kafirai ɗari biyu. Idan kuma aka samu Musulmai ɗari to za su rinjayi kafirai dubu, saboda su kafirai mutane ne waɗanda suka jahilci sakamakon da Allah yake ba wa waɗanda suka yi imani da shi suka bi dokokinsa da abin da ya tanadar wa mayaƙa don ɗaukaka addininsa.Sai daga baya kuma aka sassauta wannan hukuncin, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yanzu an sassauta musu domin ya san a cikinsu akwai raunana waɗanda ɗayansu ba zai iya karawa da kafirai goma ba shi kaɗai, to sai ya wajabta wa kowane ɗaya daga cikinsu ya tsaya ya fuskanci kafirai biyu maimakon goma, tare da yi musu albishir cewa idan akwai Musulmi masu haƙuri ɗari, to za su yi galaba a kan kafirai ɗari biyu; idan kuma akwai Musulmi dubu, to za su rinjayi kafirai dubu biyu cikin taimakon Allah, kuma Allah yana tare da masu haƙuri.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: “Lokacin da faɗar Allah ta sauka cewa: “Idan daga cikinku akwai mutum ashirin masu haƙuri, to za su rinjayi mutum ɗari biyu,” wannan hukunci ya yi wa Musulmi nauyi sosai, yayin da aka wajabta wa mutum ɗaya kada ya guje wa mutum goma. To sai sauƙi ya zo daga baya, Allah ya saukar da faɗarsa cewa: (Yanzu Allah ya sassauta muku, ya kuma san cewa a cikinku akwai raunana, saboda haka idan ya kasance akwai mutum ɗari masu haƙuri daga cikinku, to za su rinjayi kafirai ɗari biyu da izinin Allah.) To yayin da ya yi musu sassaucin adadi sai haƙuri ya ragu gwargwadon sassaucin da aka yi musu.” [Bukhari #4653].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matuƙar kafirai abokan gaba ba su bar neman Musulmi da sharri ba kuma ba su daina takalar su da faɗa ba, to bai kamata a riƙa kama su ana karɓar fansa daga wajensu ana sakin su ba; lalle a ci gaba da gamawa da su har sai an jigata su yadda ba za su iya cutar da kowa ba, sannan daga baya idan yaƙi ya ɓarke tsakaninsu da Musulmi, aka kama su ana iya sakin su bayan an karɓi fansa daga wurinsu.

2. Gargaɗi a kan masu zaƙewa wajen neman abin duniya suna mantawa da lahirarsu.

3. Idan malami ya yi ijtihadi wajen gano wani hukunci sai ya yi kuskure, to Allah ba ya kama shi da wannan kuskuren, yana yafe masa ne, har ma ya ba shi ladan ijtihadin da ya yi.

4. Ya halatta a karɓi dukiya wajen fansa, domin a nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halatta musu cin wannan dukiyar duk da cewa ya zarge su a kan sun bayar da fansa ba a lokacinta ba.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana kallon zukatan bayinsa ne yayin yi musu sakayya, idan zuciya ta gyaru, to Allah yana datar da mai ita ga samun alherin duniya da na lahira.

Suratul Anfal (67-71)

مَا كَانَ لِنَبِيٍّ أَن يَكُونَ لَهُۥٓ أَسۡرَىٰ حَتَّىٰ يُثۡخِنَ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ تُرِيدُونَ عَرَضَ ٱلدُّنۡيَا وَٱللَّهُ يُرِيدُ ٱلۡأٓخِرَةَۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٦٧ لَّوۡلَا كِتَٰبٞ مِّنَ ٱللَّهِ سَبَقَ لَمَسَّكُمۡ فِيمَآ أَخَذۡتُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ٦٨ فَكُلُواْ مِمَّا غَنِمۡتُمۡ حَلَٰلٗا طَيِّبٗاۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٦٩ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ قُل لِّمَن فِيٓ أَيۡدِيكُم مِّنَ ٱلۡأَسۡرَىٰٓ إِن يَعۡلَمِ ٱللَّهُ فِي قُلُوبِكُمۡ خَيۡرٗا يُؤۡتِكُمۡ خَيۡرٗا مِّمَّآ أُخِذَ مِنكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٧٠ وَإِن يُرِيدُواْ خِيَانَتَكَ فَقَدۡ خَانُواْ ٱللَّهَ مِن قَبۡلُ فَأَمۡكَنَ مِنۡهُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٧١

67. Bai kamata ga wani annabi ya kasance yana da wasu fursunonin yaƙi ba har sai ya yi kisan (abokan gaba) sosai a bayan ƙasa. Kuna nufin abin duniya Allah kuma Yana nufin lahira. Allah kuwa Mabuwayi ne Mai hikima.

68. Ba don wani hukunci ya riga ya gabata daga Allah ba, tabbas da azaba mai girma ta shafe ku game da abin da kuka karɓa (na fansa).

69. To sai ku ci daga abin da kuka samu na ganima halal, tsattsarka. Kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

70. Ya kai wannan Annabi, ka ce da fursunonin da suke a hannayenku: “Idan dai har Allah Ya san akwai wani alheri a zukatanku, to zai ba ku fiye da abin da aka karɓa daga wurinku Ya kuma gafarta muku. Allah kuwa Mai gafara ne Mai jin ƙai.”

71. Idan kuwa suna nufin ha'intar ka ne, to haƙiƙa da can ma sun ha'inci Allah, saboda haka Ya ɗora (ka) a kansu. Allah kuwa Masani ne Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah yana bayanin hukunce-hukuncen da suka shafi fursunonin yaƙi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, bai kamata ya kama wasu ribatattun yaƙi ba har sai ya kwarar da jini a bayan ƙasa, wato ya yaƙe su ya raunana su ya ci nasara a kansu ta yadda ba za su iya sake tsokanar Musulmi da yaƙi ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalance su da cewa, suna nufin samun wani ɗan abin duniya ne kaɗan don haka suka kama kafiran domin su biya fansa a sake su, alhali Allah yana nufin su da sakamakon lahira ne. Allah mubuwayi ne mai hikima cikin duk ayyukansa da hukunce-hukuncensa. Sannan ya bayyana cewa, ba don wani hukunci ya riga ya gabata ba daga Allah, ba shakka da wata azaba mai girma ta same su saboda kuɗin fansa da suka karɓa daga hannun kafiran Kuraishawa don su sakar musu 'yan'uwansu.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Yayin da Manzon Allah (ﷺ) ya kama fursunonin yaƙi su saba'in, sai ya nemi shawarar Abubakar da Umar (Allah ya ƙara masa yarda) a kansu. Sai Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Ya Annabin Allah, waɗannan mutane 'ya'yan baffanninka ne da danginka, ina ganin zai fi kyau ka karɓi fansa daga wurinsu ka ƙara wa mayaƙanka ƙarfi da ita; ta yiwu Allah ya shirye su su karɓi Musulunci." Sai shi kuma Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "A'a, wallahi ya Manzon Allah, ni ba na tare da ra'ayin Abubakar. Ni ina ganin ka ba mu dama mu gama da su, ka sa Aliyyu ya sare kan Aƙilu ɗan Abu Ɗalibi, ni kuma ka ba ni umarni in sare kan wane." ya ambaci sunan wani ɗan'uwansa, "Saboda waɗannan mutane su ne shugabannin kafirci kuma manyan kafirai." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya fi karkata ga shawarar Abubakar a kan ta Umar. Kashegari sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya zo ya samu Manzon Allah (ﷺ) da Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) zaune suna kuka, sai ya ce: "Ya Manzon Allah, ka faɗa min abin da kai da abokinka kuke yi wa kuka, idan na ji ni ma zan iya kukan sai in yi; idan ma na kasa yin kukan sai in ƙaƙaro shi don in taya ku." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ina kuka ne saboda shawarar da abokanka suka ba ni na karɓar fansa. Haƙiƙa an bijiro mini da azabarsu dab da ni fiye da wannan bishiyar." Ya nuna masa wata bishiya da take kusa da shi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyi. [Muslim #1763].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su ci abin da suka samu na ganima a matsayin halal tsarkakakke, su kuma kiyaye dokokin Allah, lalle Allah mai gafara ne mai jin ƙai.An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Ba a halatta wa waɗanda suka gabace mu cin dukiyar ganima ba, amma mu Allah Tabaraka wa Ta'ala ya dubi rauninmu da kasawarmu sai ya halatta mana ita." [Bukhari #3124, da Muslim #521].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi da ya faɗa wa waɗannan kamammun yaƙin Badar cewa, idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san akwai imani ingantacce a cikin zukatansu, to zai ba su abin da ya fi abin da aka karɓa daga hannuwansu na dukiyar fansa, kuma zai gafarta musu zunubbansu da suka yi a baya. Allah mai gafara ne mai jin ƙai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wasu mutanen Madina sun nemi izinin Manzon Allah (ﷺ) suka ce: "Ya Manzon Allah, ka ba mu izini mu fasa karɓar kuɗin baffanka Abbas." Sai ya ce: "Wallahi kada ku bar masa ko dirhami guda." [Bukhari #4018].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, idan so suke su ha'ince shi, to ai da ma can baya sun ha'inci Allah da kafircinsu da yaƙar Musulmi, sai Allah ya ɗora Musulmi a kansu. Allah kuma masani ne mai hikima.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya kasa muminai kashi uku:

• **Kashi na farko su** ne waɗanda suka yi hijira daga Makka zuwa Madina tun kafin yaƙin Badar har zuwa lokacin da aka gudanar da Sulhun Hudaibiyya, a shekara ta shida.

• **Kashi na biyu** su ne mutanen Madina waɗanda suka karɓi Musulunci, suka taimaki Annabi (ﷺ) da sahabbai, suka ba su masauki, suka rungume su kamar 'yan'uwansu na jini.

• **Kashi na uku** su ne Musulmi waɗanda suka ci gaba da zama a tsakiyar kafirai ba su yi hijira ba.

Don haka kashi na farko da na biyu, wato Muhajirai da Ansaru masu haɗin kai ne, masu taimakon juna ne, amma kashi na ƙarshe da suka ƙi yin hijira suka zaɓi zama a tsakiyar kafirai, to waɗannan ba su cancanci taimako ba. Amma duk da haka idan yaƙi ya haɗa su da wasu kafirai, kuma suka nemi taimakon Musulmi, to wajibi ne ga Musulmi su taimaka musu, sai dai idan akwai yarjejeniya ta zaman lafiya tsakanin Musulmi da waɗannan kafirai, to muminai bai halatta su karya wannan yarjejeniya ba.

2. Akwai babbar shaida da Allah ya yi wa *Muhajiruna* da *Ansaru* a kan cewa, su muminai ne na haƙiƙa, domin sun sadaukar da rayukansu da dukiyoyinsu don ɗaukaka addinin Allah. Hakanan waɗanda ba su sami musulunta tun farko ba sai bayan Sulhun Hudaibiyya sannan suka yi hijira, to su ma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya su cikin jerin muhajirai na farko, duk kuwa da cewa akwai tazarar daraja a tsakaninsu.

3. Wajibi ne a taimaka wa wanda aka zalunta ko da yana nesa ne.

4. Girman kula da yarjejeniya ko da da kafirai ne, da haramcin warware ta ba tare da ƙwaƙƙwarar hujja ba.

5. Watsi da soyayya da taimakon juna da rungumar kafirai da nuna musu ƙauna abu ne da yake haifar da sharri da ɓarna mai yawa tsakanin al'ummar Musulmi.

6. Duk girman matsayin mutum a wurin Allah yana buƙatar gafararsa, domin tara yake bai cika goma ba.

Suratul Anfal (72-75)

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمۡ يُهَاجِرُواْ مَا لَكُم مِّن وَلَٰيَتِهِم مِّن شَيۡءٍ حَتَّىٰ يُهَاجِرُواْۚ وَإِنِ ٱسۡتَنصَرُوكُمۡ فِي ٱلدِّينِ فَعَلَيۡكُمُ ٱلنَّصۡرُ إِلَّا عَلَىٰ قَوۡمِۭ بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَهُم مِّيثَٰقٞۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ٧٢ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٍۚ إِلَّا تَفۡعَلُوهُ تَكُن فِتۡنَةٞ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَفَسَادٞ كَبِيرٞ ٧٣ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ

وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ حَقّٗاۚ لَّهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٧٤ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنۢ بَعۡدُ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ مَعَكُمۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ مِنكُمۡۚ وَأُوْلُواْ ٱلۡأَرۡحَامِ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلَىٰ بِبَعۡضٖ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمُۢ ٧٥

72. Lalle waɗanda suka yi imani kuma suka yi hijira, suka kuma yi yaƙi da dukiyoyinsu da kuma rayukansu don Allah, da waɗanda kuma suka sauki (muminai masu hijira) suka kuma taimaka (wajen yaƙi), to waɗannan masu ƙaunar juna ne. Waɗanda kuma suka yi imani ba su kuma yi hijira ba, to babu jiɓintar al'amari a tsakaninku har sai sun yi hijira. Idan kuma suka nemi taimakonku cikin (al'amarin) addini to lalle ne ku taimake su, sai dai idan game da wasu mutane ne waɗanda yake da akwai wani alƙawari a tsakaninku da su. Allah kuma Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

73. Waɗanda kuwa suka kafirta, su masu ƙaunar juna ne. Idan ku ma ba ku aikata haka ba, to za a samu wata fitina a bayan ƙasa da kuma wata ɓarna mai girma.

74. Waɗanda kuma suka yi imani kuma suka yi hijira suka kuma yi yaƙi saboda Allah, da waɗanda kuma suka sauki (masu hijira) suka kuma taimaka, waɗannan su ne muminai na gaskiya. Suna da (sakamakon) gafara da kuma arziki na karamci.

75. Waɗanda kuma suka yi imani daga baya, suka kuma yi hijira, suka kuma yi yaƙi tare da ku, to waɗannan suna cikinku. 'Yan'uwa na jini kuma su ne suka fi cancantar (gadon) junansu a cikin Littafin Allah. Lalle Allah Masani ne ga komai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, lalle masu hijira waɗanda suka yi imani da duk abin da ya wajaba su yi imani da shi, suka bar garuruwansu da danginsu, suka ba da dukiyoyinsu don taimakon addinin Allah, kuma suka yi jihadi da rayukansu don Allah, da kuma mutanen Madina waɗanda suka ba wa Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa masu hijira masauki a gidajensu, suka taimaka musu a kan abokan gabansu, to waɗannan su ne masu ƙaunar juna.

Ibnu Kasir yana cewa: "Manzon Allah (ﷺ) ya haɗa 'yan'uwantaka tsakanin mutanen Makka masu hijira da mutanen Madina, mutum bibbiyu; suka kasance suna gadon juna fiye da yadda suke yi saboda dangantaka ta jini, har sai da Allah ya shafe wannan hukuncin da ayar gado." [Ibn Kasir, *Tafsir*, Juzi'i na 4, Shafi na 95].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Masu hijira daga Makka lokacin da suka iso Madina, Musulmin Madina yana cin gadon mai hijira ban da danginsa na jini, saboda 'yan'uwantakar da Annabi (ﷺ) ya ƙulla a tsakaninsu." [Bukhari #6747].

Wasu malamai sun ce, abin nufi da cewa "waɗannan masu ƙaunar juna ne", wato mutanen Makka da suka yiwo hijira da mutanen Madina da suka tarbe su masu taimakon junansu ne a kan mushirikai. A bisa wannan fassarar, hukuncin ayar yana nan ba a shafe shi ba. Amma yawancin malamai sun tafi ne a kan ra'ayin cewa an shafe ma'anar ayar da faɗin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cewa: "'Yan'uwa na jini su ne suka fi cancantar (gadon) junansu a cikin Littafin Allah. Haƙiƙa Allah Masanin komai ne."

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana cewa, waɗanda suka yi imani amma suka ƙi baro garuruwansu na kafirci zuwa garin Musulunci, to su muminai babu wani al'amarinsu da za su jiɓinta ko su taimaka musu har sai sun bar garuruwan kafirci sun dawo garin Musulunci. Amma idan sun nemi muminai su taimake su a kan addini to su taimaka musu, sai dai idan abokan faɗan nasu wasu kafirai ne da muminai suke da yarjejeniyar zaman lafiya tsakaninsu da su, to bai halatta su karya wannan yarjejeniya ba saboda waɗancan muminan da suka ƙi barin garuruwan kafirci. Allah mai ganin duk abin da suke aikatawa ne don haka kada su saɓa wa umarninsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗakar da muminai cewa, kafirai fa masoya ne ga junansu, to su ma muminai idan ba su aikata hakan ba, wato su ƙaunaci junansu, to lalle wata fitina za ta auku a bayan ƙasa da bazuwar ɓarna mai girma, tare da ɓata a cikin Musulmi, domin ƙarya za ta haɗe da gaskiya har wasu su kasa bambance su.

Muminai da suka yi hijira suka yi yaƙi don ɗaukaka addinin Allah da mutanen Madina waɗanda suka ba wa masu hijira masaukai, suka taimaka musu suka taimaka wa addinin Allah, to waɗannan su ne muminai na haƙiƙa, kuma suna da gafara daga Allah da arziki na karamci.

Waɗanda kuma suka yi imani bayan bayanin waɗancan hukunce-hukunce da suka gabata, kuma suka yi hijira daga garin kafirci zuwa garin Musulunci, suka kuma yi yaƙi don Allah, to waɗannan suna tare da masu hijira da mutanen Madina. Dangi su ne suka fi cancanta su gaji junansu a cikin hukuncin Allah. Lalle Allah masanin komai ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Watsi da alƙawarin da ke tsakanin Musulmi da abokan gabarsu yana kasancewa ne a cikin alƙawarin da ba a yanka masa lokaci ba, amma wanda aka riga aka yanka masa lokaci, to za a jira har sai lokacin ya ƙare ko kuma sun warware wani sharaɗi daga cikin sharuɗɗan da aka ambata lokacin ƙulla yarjejeniyar.

2. An ba mushrikai wata huɗu don su sami damar yin tunani a kan al'amarinsu, ko dai su karɓi Musulunci ko kuma su gamu da wulaƙanci na duniya da lahira.



9-Suratut Tauba

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Wannan Sura tana daga cikin surori masu sunaye da dama. Daga cikin sunayenta akwai:
- *Suratut Tauba*. Domin a cikinta an ambaci kalamar 'tuba' da yawa. Sannan an yi maganar mutanen nan uku da ba su fita yaƙin Tabuka ba, ba tare da uzuri ba, aka jinkirta tubansu har wani tsawon lokaci kafin Allah ya karɓi tuban nasu daga baya.
- Ana kiran ta da suna *'Bará'a'* saboda ta buɗe ta da wannan kalma mai nuna barranta daga mushirikai, watau tabbatar da cewa, Allah da Manzonsa ba ruwansu da su.
An karɓo daga Al-Bara'u (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Karshen Sura da ta sauka ita ce '*Suratu Bara'a*'." [Bukhari #4605, da Muslim #1618].
- Ana kiran ta '*Alfádhiha*':
An karɓo daga Sa'id ɗan Jubairu ya ce: Na tambayi Ibnu Abbas game da *Suratut Tauba*, sai ya ce: "*Tauba* ita ce *Fádhiha*." [Bukhari #4882, da Muslim#3031].
Fádhiha yana nufin bayyana abin kunyar da wani ya aikata. A cikinta ne Allah ya yi bayanin ababan kunya da munafukai suke aikatawa.
Malamai sun haɗu a kan cewa ba a fara karatun ta da '*Bisimilla*', saboda sahabbai ba su rubuta ta ba a farkon 'Mushafin Usman'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
An saukar da ita a Madina ne. Malamai da yawa sun ambato ijma'i a kan hakan.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Surar ƙarshe da ta sauka a Alƙur'ani. Ita ce Sura ta ɗari da goma sha huɗu (114). Ta sauka bayan 'Suratul Fat'h'. Malami da dama suna cewa ta sauka ne a dunƙule a lokaci guda.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Makka da Madina da Basra ayoyinta ɗari da talatin ne (130), amma a lissafin mutanen Kufa adadinsu ɗari da ashiri da tara ne (129).

5. Falalarta:
Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) yana cewa: "Ku koyi '*Suratu Bara'a*', kuma ku koyar da matanku '*Suratun Nur*'." [Sa'id bn Mansur, Tafsirinsa #1003].

6. Babban Jigonta:
• Tandar wani tsari wanda ya wajaba Musulmi su tafi a kansa wajen alaƙoƙinsu da mushirikai da ma'abota littafi da munafukai.

• Tona asirin munafukai da bayanin siffofinsu da kashe-kahensu da miyagun ayyukansu a cikin al'ummar Musulmi.
• Bayanin hukunce-hukunce masu yawa waɗanda daular Musulunci mai tasowa a wancan lokaci take da buƙata.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Raba gari tsakanin Musulmi da mushirikai da umarnin yaƙar su da watsi da sulhu da aka ƙulla da su da hana su shiga Masallaci mai alfarma.
• Ishara zuwa ga yaƙin Hunaini da darussan da ya ƙunsa game da dogaro da Allah shi kaɗai.
• Shelanta yaƙi da Larabawa ma'abota littafi har sai sun ba da jiziya da bayanin munanan maganunsu game da Uzairu da kuma Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da yadda suke cin dukiyoyin mutane ba da haƙƙi ba.
• Bayani a kan hukuncin watanni huɗu masu alfarma da rushe aƙidar Larabawa ta Jahiliyya game da waɗannan watanni.
• Taimakon Allah ga Annabinsa da babban sahabinsa Abubakar lokacin hijirarsu zuwa Madina da yadda Allah ya kare su daga kafirai.
• Bayanin siffofin munafukai da mugun tanadinsu da ƙulle-ƙullensu a kan Annabi da Musulmi da yawan rantse-rantsen ƙarya da yaɗa ɓarna a cikin al'umma da yi wa raunanan Musulmi izgili da hana nema musu gafarar Allah idan sun mutu da sauran batutuwa da suka dangance su.
• Bayanin falalar sahabban Annabi waɗanda suka fara shiga Musulunci daga cikin masu hijira da mutanen Madina.
• Ambaton ginin Masallacin Kuba a bisa ɗa'a ga Allah da taƙawa, kuma shi ne Masallacin da ya kamaci Annabi ya shiga ya yi salla a cikinsa ba masallacin munafukai da suka gina don kawo ruɗani a cikin al'umma da taimaka wa kafirai ba.
• Karɓar tubar wasu sahabbai su uku da suka ƙi halartar yaƙin Tabuka tare da Annabi ba kuma tare da sun gabatar da wani karɓaɓɓen hanzari ba. Allah ya saukar da ayoyin da suka tabbatar an yafe musu laifinsu.
• Kira ga Musulmi a kan neman ilimi na addini da karantar da shi.
• Bayanin baiwar da Allah ya yi wa muminai ta aiko musu da Manzo daga jinsinsu, wanda ya arzuta shi da kyawawan halaye da matuƙar ƙaunar al'ummarsa da tausaya musu.
Da dai sauran batutuwa da Surar ta taɓo bayani a kansu.

Suratut Tauba (1-2)

بَرَآءَةٌ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦٓ إِلَى ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّم مِّنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ١ فَسِيحُواْ فِى ٱلْأَرْضِ أَرْبَعَةَ أَشْهُرٍ وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّكُمْ غَيْرُ مُعْجِزِى ٱللَّهِ وَأَنَّ ٱللَّهَ مُخْزِى ٱلْكَٰفِرِينَ ٢

1. Allah da Manzonsa ba ruwansu da waɗanda kuka yi alƙawari da su daga cikin mushirikai.

2. To sai ku tafi ku wala a bayan ƙasa tsawon wata huɗu, kuma ku sani cewa ku ba za ku gagari Allah ba, kuma lalle Allah Mai wulaƙanta kafirai ne.

A ayoyi goma sha biyar na farkon wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, shi da Manzonsa (ﷺ) ba ruwansu da alƙawarin da yake tsakanin Musulmi da mushirikai na zaman lafiya, sakamakon warware sharuɗɗan zaman lafiya da su mushirikai suka yi. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su tsawon wata huɗu su yi yawo a bayan ƙasa, su je duk inda suke so babu wani Musulmi

da zai taɓa su. Lokacin kuma ya fara ne daga ranar sallar layya ta shekara ta tara, ya kuma ƙare a ranar goma ga watan Rabi'ul Akhir a shekara ta goma.
Sai kuma Allah ya ja hankalinsu da cewa, su sani fa ba za su iya gagarar Allah ba, ba za su iya kuɓuce wa uƙubarsa ba idan ya yi nufin kama su. Kuma su sani Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai wulaƙanta kafirai ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wata yarjejeniya mai ƙayyadajjen lokaci, ba ya halatta a warware ta kafin cikar lokacinta, amma da sharaɗin cewa su ma abokan gaba su kiyaye wannan sharaɗin kada su karya shi. Idan kuwa suka saɓa wa wani sharaɗi daga cikin sharuɗɗan da aka yi da su, to sun warware alƙawarin da aka yi da su kenan.

2. Yana daga cikin abin da yarjejeniyar zaman lafiya take warwarewa a dalilinsu, idan abokan yarjejeniya suka taimaka wa abokan faɗan Musulmi, to sun warware wannan alƙawari.

3. Kwaɗaitarwa a kan tuba zuwa ga Allah da nisantar aikata shirka.

4. Duk wanda ya bijire wa Allah da Manzonsa (ﷺ) to ya sani ba zai gagari Allah ba.

Suratut Tauba (3-4)

وَأَذَٰنٌ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦٓ إِلَى ٱلنَّاسِ يَوْمَ ٱلْحَجِّ ٱلْأَكْبَرِ أَنَّ ٱللَّهَ بَرِيٓءٌ مِّنَ ٱلْمُشْرِكِينَ وَرَسُولُهُۥ ۚ فَإِن تُبْتُمْ فَهُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ ۖ وَإِن تَوَلَّيْتُمْ فَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّكُمْ غَيْرُ مُعْجِزِى ٱللَّهِ ۗ وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ۝٣ إِلَّا ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّم مِّنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ثُمَّ لَمْ يَنقُصُوكُمْ شَيْـًٔا وَلَمْ يُظَٰهِرُواْ عَلَيْكُمْ أَحَدًا فَأَتِمُّوٓاْ إِلَيْهِمْ عَهْدَهُمْ إِلَىٰ مُدَّتِهِمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُتَّقِينَ ۝٤

3. Kuma sanarwa daga Allah da Manzonsa zuwa ga mutane ranar Babbar Salla cewa, lalle Allah da Manzonsa babu ruwansu da mushrikai. Amma idan kuka tuba, to shi ya fi alheri a gare ku, idan kuma kuka ba da baya, to ku sani lalle ku fa ba za ku gagari Allah ba. Kuma ka yi albishir ga waɗanda suka kafirta da azaba mai raɗadi.

4. Sai fa waɗannan mushrikan da kuka yi alƙawari da su sannan kuma ba su rage muku wani abu ba (daga alƙawarin), ba su kuma taimaka wa wani a kanku ba, to sai ku cika musu alƙawarinsu har zuwa lokacinsu (da kuka ayyana). Lalle Allah Yana son masu taƙawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, wannan sanarwa ce daga Allah da Manzonsa zuwa ga mutane baki ɗaya, Musulmai da kafirai, a ranar sallar layya cewa, Allah ba ruwansa da mushirikai, hakanan Manzonsa ma ba shi ba su. Don haka idan sun yarda sun tuba, to hakan shi ne mafi alheri gare su, idan kuwa sun bijire to su sani cewa ba za su gagari Allah ba, kuma ba za su kuɓuta daga azabarsa ba. Don haka Annabi (ﷺ) ya yi wa kafirai albishir da wata azaba mai raɗaɗi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya togace wasu daga cikin kafirai waɗanda da ma akwai alƙawari tsakaninsu da muminai sannan suka cika wannan alƙawarin ba su warware shi ba; to waɗannan wajibi ne a kan muminai su cika musu alƙawarinsu har zuwa lokacin da aka yanka tsakaninsu da mushrikai ya zo ƙarshe. Lalle Allah yana son masu kiyaye dokokinsa kuma masu cika alƙawari ba sa warware shi.

An karɓo daga Humaidu ɗan Abdurrahman ɗan Auf cewa, Abu Huraira yana cewa: Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya aike ni tare da masu shela a wannan aikin hajjin mu yi shela a Mina cewa: Daga

wannan shekarar kada wani mushiriki ya sake zuwa aikin hajji, kuma kada wani ya sake yin ɗawafi a Ɗakin Allah tsirara. Sannan Manzon Allah (ﷺ) ya sake turo Aliyyu ɗan Abu Ɗalibi (Allah ya ƙara masa yarda) daga bisani ya sake yin wata shela cewa, ba ruwan Allah shi da Manzonsa da mushrikai. Abu Huraira ya ce: Sai Aliyyu ya yi shela tare da mu a ranar sallar layya ga mahajjata a Mina ya bayyana wannan bara'ar, kuma daga wannan shekarar kada wani mushiriki ya sake zuwa aikin hajji, kuma kada wani ya sake yin ɗawafi tsirara a Ɗakin Allah. [Bukhari #4655, da Muslim #1347].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin yaƙar mushirikai masu yaƙar Musulmi a ko'ina suke matuƙar ba su daina yaƙar Musulmi ba.

2. Halaccin kama mushrikai a matsayin fursinonin yaƙi.

3. Girman lamarin salla, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya ta sharaɗin farko na barin yaƙar mushirikai tare da ba da zakka daga wanda yake da dukiya.

4. Nuni zuwa ga muhimmancin samar da tsaro a ƙasashen Musulmi da toshe duk wata kafa da abokan gaba za su shigo wa Musulmi.

5. Idan shugaba ko wani Musulmi ya ba wa wani kafiri aminci, to wajibi ne sauran Musulmi su girmama wannan amincin kada su cutar da wannan kafirin.

6. Alƙur'ani ba wata halittar Allah ne ba, maganarsa ce; maganar Allah kuwa siffarsa ce. Don haka Alƙur'ani da muke karantawa maganarsa ce, amma muryar ta mai karatu ce.

Suratut Tauba (5-6)

فَإِذَا ٱنسَلَخَ ٱلۡأَشۡهُرُ ٱلۡحُرُمُ فَٱقۡتُلُواْ ٱلۡمُشۡرِكِينَ حَيۡثُ وَجَدتُّمُوهُمۡ وَخُذُوهُمۡ وَٱحۡصُرُوهُمۡ وَٱقۡعُدُواْ لَهُمۡ كُلَّ مَرۡصَدٖۚ فَإِن تَابُواْ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ فَخَلُّواْ سَبِيلَهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٥ وَإِنۡ أَحَدٞ مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ٱسۡتَجَارَكَ فَأَجِرۡهُ حَتَّىٰ يَسۡمَعَ كَلَٰمَ ٱللَّهِ ثُمَّ أَبۡلِغۡهُ مَأۡمَنَهُۥۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَعۡلَمُونَ ٦

5. To idan watanni masu alfarma suka wuce sai ku yaƙi mushrikai a duk inda kuka same su, ku kuma kama su ku tsare su ku kuma toshe musu kowace hanya. To amma idan sun tuba sun kuma tsai da salla kuma sun ba da zakka, to sai ku ƙyale su. Lalle Allah Mai gafara ne Mai jin ƙai.

6. Kuma idan wani daga mushrikai ya nemi mafaka a wurinka to sai ka ba shi mafaka har ya samu damar jin zancen Allah, sannan ka isar da shi wurin amincewarsa. Wannan kuwa saboda lalle su mutane ne da ba sa sanin (gaskiya).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai su kashe abokan gabarsu mushirikai duk inda suka same su bayan watanni masu alfarma sun shuɗe, kuma su kama su a matsayin fursinonin yaƙi, su kuma takura musu, su hana su yawatawa a bayan ƙasa, ko shigowa inda suke, su saka musu tsattsauran takunkumi, su tare duk wata hanyar bin su don su kama su su kashe ko su ɗaure. To amma idan sun tuba sun tsayar da sallolin farilla tare da cika sharuɗɗanta, suka kuma bayar da zakka ga waɗanda suka cancanta a ba, to sai Musulmi su ƙyale su kada su taɓa su. Lalle Allah mai gafara ne mai jin ƙai.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bai wa Annabi (ﷺ) damar ya bayar da mafaka ga duk wani mushiriki da ya nemi a ba shi mafaka domin ya sami damar sauraren Alƙur'ani. Idan ya ƙi musulunta, to ya ƙyale shi ya koma ƙasarsa inda zai samu mafaka. Saboda su mutane ne waɗanda ba su san komai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cika alƙawari yana daga cikin kyawawan halayen Musulmi.

2. Duk wanda za a yi yarjejeniyar zaman lafiya da shi, a ba shi aminci, amma ya riƙa fitowa yana sukan Musulunci da Musulmai, ba tare da la'akari da alƙawari ko kusancin da ke tsakaninsa da Musulmi ba, to irin wannan mutum idan ya samu galaba a kan Musulmi ba zai taɓa la'akari da wani alƙawari ko kusanci ba.

3. Ba duka kafirai ne suka taru suka zama ɗaya ba; a cikinsu akwai masu alƙawari da mutunci da riƙe amana; akwai kuma marasa mutunci, maciya amana, waɗanda babu wani abu da zai hana su yin ha'inci. Shi ya sa Allah ya ce: "Yawancinsu fasiƙai ne," bai ce dukansu ba, domin 'fasiƙanci' a nan yana nufin saba alƙawari.

Suratut Tauba (7-8)

كَيۡفَ يَكُونُ لِلۡمُشۡرِكِينَ عَهۡدٌ عِندَ ٱللَّهِ وَعِندَ رَسُولِهِۦٓ إِلَّا ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّمۡ عِندَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۖ فَمَا ٱسۡتَقَٰمُواْ لَكُمۡ فَٱسۡتَقِيمُواْ لَهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَّقِينَ ٧ كَيۡفَ وَإِن يَظۡهَرُواْ عَلَيۡكُمۡ لَا يَرۡقُبُواْ فِيكُمۡ إِلّٗا وَلَا ذِمَّةٗۚ يُرۡضُونَكُم بِأَفۡوَٰهِهِمۡ وَتَأۡبَىٰ قُلُوبُهُمۡ وَأَكۡثَرُهُمۡ فَٰسِقُونَ ٨

7. Ta yaya zai yiwu a samu wani alƙawari tsakanin Allah da Manzonsa da kuma mushirikai in ban da waɗanda kuka yi alƙawari da su a Masallaci mai alfarma? To matuƙar sun tsaya muku (bisa gaskiya) sai ku ma ku tsaya musu. Lalle Allah Yana son masu taƙawa.

8. Ta yaya?! (haka zai faru) alhali idan suka yi nasara a kanku ba za su duba wani kusanci ba balle wani alƙawari game da ku? Suna yardar da ku ne da bakunansu, alhali kuwa zukatansu suna ƙi. Yawancinsu kuma fasiƙai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana dalilan da suka sa shi da Manzonsa (ﷺ) suka yi watsi da yarjejeniyar da suka ƙulla da kafirai. Allah kuma ya ba da umarnin yaƙar su da kama su. Yaya ma za a yi mushirikai su ƙulla wani alƙawari na zaman lafiya tsakaninsu da Allah da Manzonsa? Wannan ba abu ne mai yiwuwa ba, domin su mutane ne mayaudara, maciya amana. Don haka wajibi ne muminai su yaƙe su duk inda suka haɗu da su, sai dai an toge wasu mushirikai da suka yi yarjejeniyar zaman lafiya da su a Masallaci mai alfarma a ranar Sulhun Hudaibiyya, to matuƙar su sun tsaya a kan wannan alƙawarin ba su karya shi ba, to su ma Musulmi su tsaya musu a kansa ƙada ku karya shi, har zuwa lokacin ƙarewarsa. Lalle Allah yana son masu kiyaye dokokinsa.
Annabi (ﷺ) ya yi alƙawarin zaman lafiya da ƙabilun Banu Bakra masu ƙawance da Kuraishawa a ranar Sulhun Hudaibiyya na tsawon lokacin da suka yi da Kuraishawan kansu. To bai warware wannan alƙawari ba, har sai da ƙabilar Kuraishawa da ƙabilar Banud Dil ɗan Bakara suka warware nasu. Sai Allah ya yi umarni da a cika wa sauran ƙabilun Banu Bakra alƙawarinsu har ƙarshen lokacin da aka ɗeba musu. Sannan Allah ya ci gaba da bayanin cewa, ta yaya ma wani alƙawarin zaman lafiya zai samu ga mushirikai waɗanda, idan suka samu nasara a kan muminai ba za su tausaya musu ko kaɗan ba, ba kuma za su duba

wani kusanci ko dangantaka ko wani alƙawari ba? Da bakunansu kam za su riƙa faɗa wa muminai maganganu masu daɗi don su yarda da su, amma zukatansu sun ƙi amincewa da abin da bakunansu suke faɗa. Yawancincu kuma fasiƙai ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin yanke zumunci da warware alƙawari.

2. Kiyayyar kafirai ga Musulmi saboda imaninsu ne ba don wani abu ne daban ba.

3. Salla da zakka tare suke da Kalmar Shahada wajen hana yaƙar mutum.

4. ‘Yan’uwantaka ta Musulunci tana tabbata ne ga waɗanda suka tsayar da salla suka bayar da zakkar dukiyoyinsu. Wanda ba shi da kuɗin fitar da zakkar to wajibi ne ya yarda da wajabcinta.

5. Yana daga farkon kyawawan ɗabi’u na Musulunci, ‘yan’uwantaka ta addini, abin da mushirikai suka rasa, don haka yaƙe-yaƙe tsakaninsu ba sa ƙarewa.

6. Yaƙi a Musulunci ana yin sa ne don tabbatar da gaskiya da hana ɓarna da zalunci.

7. Alƙawarin da ke kare mushiriki yana yankewa ne da zarar ya shiga sukar addinin Musulunci da zagin Annabi (ﷺ) da sukan Alƙur’ani.

8. Duk wanda yake zagin Musulunci da ɓata shi, to wannan ya zama jigo a kafirci.

Suratut Tauba (9-12)

ٱشۡتَرَوۡاْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ ثَمَنٗا قَلِيلٗا فَصَدُّواْ عَن سَبِيلِهِۦٓۚ إِنَّهُمۡ سَآءَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩ لَا يَرۡقُبُونَ فِي مُؤۡمِنٍ إِلّٗا وَلَا ذِمَّةٗۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُعۡتَدُونَ ١٠ فَإِن تَابُواْ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ فَإِخۡوَٰنُكُمۡ فِي ٱلدِّينِۗ وَنُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ١١ وَإِن نَّكَثُوٓاْ أَيۡمَٰنَهُم مِّنۢ بَعۡدِ عَهۡدِهِمۡ وَطَعَنُواْ فِي دِينِكُمۡ فَقَٰتِلُوٓاْ أَئِمَّةَ ٱلۡكُفۡرِ إِنَّهُمۡ لَآ أَيۡمَٰنَ لَهُمۡ لَعَلَّهُمۡ يَنتَهُونَ ١٢

9. Sun musanya ayoyin Allah da ɗan kuɗi ƙanƙani, sannan suka toshe hanyarsa. Lalle su dai abin da suke aikatawa ya munana.

10. Ba sa duban wani kusanci na zumunci da wani mumini ballantana kuma wani alƙawari. Waɗannan kuma su ne masu ƙetare iyaka.

11. To idan sun tuba, suka kuma tsayar da salla kuma suka ba da zakka, to sun zama ‘yan’uwanku a cikin addini. Muna kuwa bayanin ayoyi ne filla-filla ga mutane da suke da sani.

12. Idan kuma suka warware rantsuwarsu bayan ɗaukar alƙawarinsu, suka kuma soki addininku, to sai ku yaƙi shugabannin kafirci, don kuwa ba su da alƙawari, ko yin haka zai sa su daina.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, mushirikai sun musanya ayoyin Allah da wani jin daɗi kaɗan na duniya, don haka suka hana kawunansu karɓar gaskiya kuma suka hana wasu su karɓa. Lalle wannan abin da suke yi ya yi muni matuƙa. Idan kuwa sun yi nasara a kan wani

mumini, to fa ba ruwansu da duba Allah ko kusanci ko alƙawari. Ba shakka waɗannan mutane sune ‘yan ta’adda.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa muminai cewa, idan mushirikai suka tuba suka bar shirka, kuma suka tsayar da sallolin farilla yadda ya dace, suka fitar da zakkar dukiyoyinsu, to sun zama ‘yan’uwan muminai a Musulunci, domin Allah yana bayanin ayoyi ne ga mutanen da suke sanin gaskiya suke yin aiki da ita.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara da cewa, idan mushirikai suka karya alƙawarin da suka yi da Musulmi, suka soki addininsu suka wulaƙanta shi, to Musulmi su fito su yaƙi shugabannin kafirci, don kuwa sun nuna alƙawarin da suka ɗauka ba da gaske suke ba. Wannan shi zai sa su daina abin da suke yi na kafirci da ɓata Musulunci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yaƙar kafiran da suka ci amanar Musulmi suka karya alƙawarin sulhu da ke tsakaninsu ya fi yaƙar waɗanda ba su ba.

2. Wajibi ne Musulmi ya ji tsoron Allah shi kaɗai kada ya fifita tsoron wani a kan na Allah.

3. Jarumta da rashin tsoro wajen taimakon addini alama ce ta ƙarfin imani.

4. Wanda ya fara tsokana shi ne ya fi girman laifi.

5. Yana daga cikin manufofin shari’a kawar da damuwar muminai da duk wani ƙunci a zukatansu. Wannan shi ya nuna soyayyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a gare su.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin zai tafiyar wa muminai damuwarsu ya huce musu haushinsu. Kuma hakan ya tabbata. Wannan wata mu’ujiza ce ga Annabi (ﷺ).

7. Tafiyar wa da sahabbai damuwarsu da huce musu haushinsu yana nuna su muminai ne na haƙiƙa a wurin Allah. Kuma haka ya nuna zukatansu na cike da damuwa saboda wulaƙancin da kafirai suke yi wa Musulunci da kuma matuƙar ƙaunarsu ga ɗaukakar wannan addini. Wannan hali ne da babu mai siffantuwa da shi sai mumini.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai wajabta yin jihadi don a zubar da jini ba kawai; ya wajabta shi ne don a yi shi don Allah shi kaɗai tare da kiyaye dokokinsa da bin umarninsa. Don haka duk masu yaƙi don wasu manufofi daban ba waɗannan ba, to ba jihadi suke yi ba.

9. Allah ya wajabta yin jihadi don ya tantance tsakanin muminai na gaskiya da waɗanda ba na gaskiya ba.

Suratut Tauba (13-16)

أَلَا تُقَٰتِلُونَ قَوۡمٗا نَّكَثُوٓاْ أَيۡمَٰنَهُمۡ وَهَمُّواْ بِإِخۡرَاجِ ٱلرَّسُولِ وَهُم بَدَءُوكُمۡ أَوَّلَ مَرَّةٍۚ أَتَخۡشَوۡنَهُمۡۚ فَٱللَّهُ أَحَقُّ أَن تَخۡشَوۡهُ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١٣ قَٰتِلُوهُمۡ يُعَذِّبۡهُمُ ٱللَّهُ بِأَيۡدِيكُمۡ وَيُخۡزِهِمۡ وَيَنصُرۡكُمۡ عَلَيۡهِمۡ وَيَشۡفِ صُدُورَ قَوۡمٖ مُّؤۡمِنِينَ ١٤ وَيُذۡهِبۡ غَيۡظَ قُلُوبِهِمۡۗ وَيَتُوبُ ٱللَّهُ عَلَىٰ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ١٥ أَمۡ حَسِبۡتُمۡ أَن تُتۡرَكُواْ وَلَمَّا يَعۡلَمِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ جَٰهَدُواْ مِنكُمۡ وَلَمۡ يَتَّخِذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَا رَسُولِهِۦ وَلَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَلِيجَةٗۚ وَٱللَّهُ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٦

13. Yanzu ba za ku yaƙi mutanen da suka warware alƙawarinsu ba, kuma (tun farko) sun yi nufin fitar da Manzo (daga Makka), su ne kuma suka fara far muku da yaƙi? Yanzu kwa riƙa tsoron su? To Allah ne Ya fi cancantar ku ji tsoron Sa idan kun kasance muminai.

14. Ku yaƙe su, Allah zai azabtar da su ta hannayenku, Ya kuma kunyatar da su, kuma Ya taimake ku a kansu, Ya kuma warkar da zukatan muminai.

15. Ya kuma tafiyar da ɓacin ransu. Allah kuma Ya karɓi tuban duk wanda Ya ga dama. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima.

16. Ko kuwa kuna tsammanin za a ƙyale ku ne (sakaka) alhali kuwa har yanzu Allah bai tantance waɗanda suka yi jihadi ba a cikinku, ba su kuma riƙi wasu masoya ba banda Allah da Manzonsa da muminai? Allah Mai cikakken sanin abin da kuke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa muminai cewa, me zai hana su yaƙi mushrikan da suka karya alƙawarin zaman lafiya da ke tsakaninsu suka yi niyyar korar Annabi (ﷺ) daga garin Makka, kuma su ne suka fara karya yarjejeniyar zaman lafiyar da aka yi da su lokacin da suka yaƙi ƙabilar *Khuza'ah* waɗanda su kuma suke da ƙawance da Musulmi? Shin yanzu muminai suna jin tsoron su ne? To ai Allah ne ya fi cancanta su ji tsoro idan har sun kasance muminai na gaskiya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su yaƙi waɗannan kafirai masu karya alƙawari; Allah ne zai azabtar da su ta hannayen muminai ya wulaƙanta su, ya ba muminai nasara a kansu, ya kuma warkar da zukatan muminai ta hanyar kawar musu da damuwa, ya tafiyar da ɓacin ransu. Allah kuma shi yake karɓar tubar wanda ya ga dama daga cikin mushirikai, kuma Allah masani ne mai hikima.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa kafirai cewa, shin suna zaton zai ƙyale su ne hakanan ba tare da ya jarrabe su da jihadi ba, don ya rarrabe tsakanin masu gaskiya wajen jihadinsu don Allah ba su riƙi wasu masoya na kusa a cikin kafirai ba maimakon Allah da Manzonsa da muminai waɗanda za su riƙa bayyana musu sirrin Musulmi? Allah mai cikakken sani ne game da duk abin da suke aikatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Aya ta (17) tana nuna ba a yarda wani kafiri ya gina wa Musulmi masallaci ba.

2. Kyawawan ayyukan kafirai komi yawansu ba su da lada a wurin Allah.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai su raya masallatai, hakan ya haɗa da sake gina inda ya rushe daga cikinsu da tsabtace su da sanya musu fitilu da turare da girmama su da aiwatar da ibadu a cikinsu kamar salla da ambaton Allah da karatun Alƙur'ani da karantar da littattafan ilimin addinin Musulunci.

4. Masu raya masallatai na gaskiya su ne masu imani na gaskiya, masu ayyuka na ƙwarai da tsoron Allah wanda shi ne tushen duk wani alheri.

5. Wani daga cikin magabata yana cewa: "Idan kuka ga wanda yake raya masallaci, to ku kyautata masa zato." Wannan ayar ta 18 tana tabbatar da wannan magana.

6. An haɗa imani da Allah tare da imani da ranar lahira a wurare da dama na Alƙur'ani. Dalili kuwa shi ne kafirce wa ranar lahira shi ne musabbabin duk wani sharri da ɓarna a duniya. Domin wanda bai yi imani da ranar lahira ba, to ba zai tsoraci azabar da take cikinta ba, ba kuma zai yi kwaɗayin samun ni'imarta ba.

7. Watakila hikimar da ke cikin haɗa ambaton bayar da zakka tare da batun raya masallatai ita ce, saboda kasancewar masallatai matattara ce ta mutane daban-daban, waɗanda haɗuwarsu za ta bayar da dama a iya tantance mawadaci da mabuƙaci, a san waɗanda za a karɓo zakka daga hannuwansu da waɗanda za a raba wa.

Suratut Tauba (17-19)

مَا كَانَ لِلۡمُشۡرِكِينَ أَن يَعۡمُرُواْ مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ شَٰهِدِينَ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِم بِٱلۡكُفۡرِۚ أُوْلَٰٓئِكَ حَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡ وَفِي ٱلنَّارِ هُمۡ خَٰلِدُونَ١٧ إِنَّمَا يَعۡمُرُ مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَأَقَامَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَى ٱلزَّكَوٰةَ وَلَمۡ يَخۡشَ إِلَّا ٱللَّهَۖ فَعَسَىٰٓ أُوْلَٰٓئِكَ أَن يَكُونُواْ مِنَ ٱلۡمُهۡتَدِينَ١٨ ۞أَجَعَلۡتُمۡ سِقَايَةَ ٱلۡحَآجِّ وَعِمَارَةَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِ كَمَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَجَٰهَدَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ لَا يَسۡتَوُۥنَ عِندَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ١٩

17. Ba zai taɓa yiwuwa mushrikai su raya masallatan Allah ba, alhalin kuwa suna masu iƙirarin kafirci ga kawunasu. Waɗannan ayyukansu sun ɓaci kuma a cikin wuta za su dawwama.

18. Lalle mai raya masallatan Allah shi ne kawai wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira ya kuma tsayar da salla, kuma ya ba da zakka, bai kuma ji tsoron wani ba sai Allah. To waɗannan tabbas suna cikin shiryayyu.

19. Yanzu kwa mayar da shayar da alhazai da raya Masallaci mai alfarma kamar wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira ya kuma yi jihadi saboda Allah? Ai ba za su zama ɗaya ba a wurin Allah. Allah kuma ba Ya shiryar da mutane azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, ba zai yiwu mushirikai su raya masallatan Allah ta hanyar gina su da bauta wa Allah a cikinsu da tsabtace su ba, alhalin suna yi wa kawunansu shaida da kafirci, wato suna iƙirarin bautar gumaka da ƙaryata manzancin Annabi (ﷺ), to waɗannan ayyukansu sun ɓaci kuma za su shiga wutar Jahannama su dawwama a cikinta har abada.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, masallatai dai na Allah ne, wanda kawai yake raya su shi ne wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, ya kuma tsayar da sallar farilla da rukunanta, ya ba da zakka, kuma ba ya jin tsoron kowa sai Allah; to waɗannan tabbas sune shiryayyu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Mutum bakwai Allah zai saka su a inuwarsa ranar gobe ƙiyama…." daga cikinsu ya ambaci "….mutumin da zuciyarsa ta rataya da masallaci." [Bukhari #6806, da Muslim #1031].

An karɓo daga Usman ɗan Affanu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Wanda ya gina masallaci don Allah, to Allah zai gina masa kwatankwacinsa a Aljanna." [Bukhari #450 da Muslim #533].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi mutane cewa, ta yaya za su gwada mutanen da suke shayar da alhazai ruwa a lokacin hajji da kula da masallaci mai alfarma da mutumin da ya yi imani da

Allah da ranar lahira, ya kuma yi jihadi don ɗaukaka kalmar Allah? A'a; waɗannan ba za su taɓa zama ɗaya ba a wurin Allah. Allah kuma ba ya shiryar da mutanen da suke azzalumai.

An karɓo daga An-Nu'uman ɗan Bashiru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Ina zaune a kusa da minbarin Manzon Allah (ﷺ), sai wani mutum ya ce: "Babu abin da zai dame ni don ban yi wani aiki bayan musuluntata ba sai dai shayar da alhazai." Wani kuma ya ce: "Babu abin da zai dame ni don ban yi wani aiki bayan musuluntata ba, sai dai in raya masallaci mai alfarma." Sai kuma wani ya ce: "Jihadi don Allah ya fi duk abin da kuka faɗa." Sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya daka musu tsawa ya ce: "Ku ɗaina ɗaga muryoyinku a wajen minbarin Manzon Allah (ﷺ), ga shi kuma yau Juma'a ce, amma idan na gama sallar Juma'a zan shiga wurin Manzon Allah (ﷺ) in yi masa fatawa game da abin da kuka yi saɓani a kai." Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan aya ta 19." [Muslim #1879].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman darajar sahabban Annabi (ﷺ).

2. Bin tafarkin sahabban Annabi (ﷺ) shi ne bin tafarkin shiga Aljanna.

3. Aljanna gidan ni'ima ce wadda ba ta ƙarewa.

4. Imanin mutum ba ya cika da faɗar Kalmar Shahada ita kaɗai ba tare da ya yi ayyuka na ƙwarai ba.

5. Yayin da sahabbai suka siffantu da manya-manyan siffofi guda uku, watau imani da yin hijira da kuma jihadi da dukiya da rayuwa, sai aka saka musu da manya-manyan sakamako iri uku, watau rahamar Allah da yardarsa da kuma gidajen Aljanna masu cike da ni'imomi na har abada.

Suratut Tauba (20-22)

ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ أَعۡظَمُ دَرَجَةً عِندَ ٱللَّهِۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ٢٠ يُبَشِّرُهُمۡ رَبُّهُم بِرَحۡمَةٖ
مِّنۡهُ وَرِضۡوَٰنٖ وَجَنَّٰتٖ لَّهُمۡ فِيهَا نَعِيمٞ مُّقِيمٞ٢١ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥٓ أَجۡرٌ عَظِيمٞ٢٢

20. Waɗanda suka yi imani kuma suka yi hijira suka yi jihadi saboda Allah da dukiyoyinsu da kawunansu su suka fi girman daraja a wurin Allah kuma waɗannan su ne marabauta.

21. Ubangijinsu Yana yi musu albishir da rahama da yarda daga gare Shi, kana da gidajen Aljanna (waɗanda) a cikinsu suke da ni'imomi masu ɗorewa.

22. Su madawwama ne a cikinsu har abada. Lalle lada mai girma yana wurin Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, lalle sahabban Annabi (ﷺ) waɗanda suka yi imani kuma suka baro gidajensu suka yi hijira tare da Manzon Allah (ﷺ) zuwa Madina, kuma suka yi jihadi da dukiyoyinsu da rayukansu don Allah, waɗannan sun fi ɗaukakar matsayi a wurin Allah fiye da mushirikai masu shayar da alhazai ruwa a lokacin aikin hajji da masu raya Masallaci. Waɗancan sahabban su ne masu samun babban rabo. Ubagijinsu yana yi musu albishir na samun wata rahama daga gare shi da yarda da su da kuma gidajen Aljanna masu cike da ni'imomi masu ɗorewa har

abada, kuma za su zauna a cikinsu har abada. Lalle lada mai girma yana wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah zai ce da 'yan Aljanna: "Ya ku 'yan Aljanna." Sai su ce: "Amsawarka ya Ubangijinmu tare da biyayya bayan biyayya kuma a hannunka alheri yake." Sai ya ce: "Kun yarda da sakamakon da na ba ku?" Sai su ce: "Me zai hana mu yarda ya Ubangiji, alhalin ka ba mu abin da ba ka ba wani daga cikin halittunka ba?" Sai ya ce: "Ba na ba ku abin da ya fi haka ba?" Sai su ce: "Ya Ubangiji, mene ne ya fi hakan?" Sai ya ce: "In yarda da ku, ba zan taɓa yin fushi da ku ba bayan haka har abada." [Bukhari #7518 da Muslim #2829].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi a kan jiɓintar waɗanda suka fifita son kafirci a kan imani a fili ko a ɓoye.

2. Kusanci na aƙida ya fi kusanci na jini da dangantaka. Idan aƙida ta sha bamban to babu sauran wata jiɓinta da ƙawance, ko da kuwa tare da dangi ne na jini.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci iyaye da 'yan'uwa a aya ta 23 bai ambaci 'ya'ya ba, saboda iyaye su ne masu faɗa a ji su ne abokan shawara, amma 'ya'ya sau tari su mabiya ne.

4. Hakanan ya ambaci iyaye maza amma bai ambaci mata ba, saboda maza su ne suke yaƙi, don haka sau tari su ne masu neman taimako da agaji, don haka ya taƙaita a kan ambaton su kaɗai.

5. Idan an hana jiɓintar iyaye da 'yan'uwa tare da kusancin dagantakarsu, to waɗanda ba su kai su a matsayin dangantaka ba su suka fi cancanta aguji jiɓintar su.

6. Idan aka samu karo tsakanin wata maslaha guda ɗaya ta addini da wasu muhimman abubuwa na rayuwar duniya, to wajibi ne a gabatar da maslahar addini a kansu.

7. Wajabcin son Allah da Manzonsa (ﷺ) da fifita son su a kan komai, da tsananin narko na azaba ga duk wanda ya fifita son wani abu daga cikin abubuwa takwas da aka ambata a aya ta 24.

8. A nan ba wai ana nufin mutum ya ƙaurace wa iyalansa da danginsa ne ba, ko ya yi watsi wa dukiyarsa da kasuwancinsa da gidaje masu kyau ba. Yin haka ba ya daga cikin koyarwar Musulunci. Abin da ake buƙata wajen Musulmi shi ne ya sanya son Allah da Manzonsa da addininsa a zuciyarsa fiye da sonsa ga waɗancan abubuwa.

9. Duk wanda ya fifita biyayyar wani a kan biyayyar Allah da Manzonsa (ﷺ), ko maganar wani a kan ta Allah da Manzonsa, ko yardar wani a kan yardarsu, ko tsoron wani a kan tsoron Allah, ko ya dogara ga wani ba Allah ba, to wannan ya zama wanda bai fifita son Allah da Manzonsa a kan son komai ba. Ko da ya faɗa da harshensa cewa shi ya fi son su, to ƙarya ce yake.

10. A aya ta 24 an ambaci 'ya'ya ba kamar aya ta 23 ba, saboda a nan ana zancen 'soyayya' ne; soyayyar 'ya'ya kuwa tana da cin rai matuƙa. A baya kuwa an ambaci iyaye domin magana ce a kan masu faɗa a ji ko abokan shawara.

11. An haɗa son Allah tare da son Annabi (ﷺ) domin son Allah ba zai cika ba har sai mutum ya so abin da yake so, ya ƙi abin da yake ƙi. Kuma babu wata hanyar sanin abin da Allah yake so ko yake ƙi sai ta

hanyar Annabi (ﷺ), domin shi ne mai isar da saƙo daga Allah. Don haka son Allah ba zai tabbata ba sai tare da son Manzon Allah (ﷺ).

Suratut Tauba (23-24)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُوٓاْ ءَابَآءَكُمۡ وَإِخۡوَٰنَكُمۡ أَوۡلِيَآءَ إِنِ ٱسۡتَحَبُّواْ ٱلۡكُفۡرَ عَلَى ٱلۡإِيمَٰنِۚ وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٢٣ قُلۡ إِن كَانَ ءَابَآؤُكُمۡ وَأَبۡنَآؤُكُمۡ وَإِخۡوَٰنُكُمۡ وَأَزۡوَٰجُكُمۡ وَعَشِيرَتُكُمۡ وَأَمۡوَٰلٌ ٱقۡتَرَفۡتُمُوهَا وَتِجَٰرَةٌ تَخۡشَوۡنَ كَسَادَهَا وَمَسَٰكِنُ تَرۡضَوۡنَهَآ أَحَبَّ إِلَيۡكُم مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَجِهَادٖ فِي سَبِيلِهِۦ فَتَرَبَّصُواْ حَتَّىٰ يَأۡتِيَ ٱللَّهُ بِأَمۡرِهِۦۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡفَٰسِقِينَ ٢٤

23. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ɗauki iyayenku da ‘yan’uwanku masoya muddin dai sun fifita kafirci a kan imani. Duk kuwa waɗanda suka ɗauke su (masoya) daga cikinku to waɗannan su ne azzalumai.

24. Ka ce: “Idan iyayenku da ‘ya’yanku da ‘yan’uwanku da matanku da danginku da dukiyoyin da kuka tara da kasuwanci da kuke tsoron gurguncewarsa da kuma gidajen da kuke sha'awa; idan har su kuka fi so fiye da Allah da Manzonsa da kuma jihadi saboda Shi, to sai ku saurara har Allah Ya zo da al’amarinsa. Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane fasiƙai.”

A waɗannan ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana muminai su ɗauki iyayensu ko ‘yan’uwansu na jini su zama majiɓinta al’amuransu muddin sun fifita kafirci a kan imani, ya kuma bayyana cewa duk wanda ya jiɓince su to waɗannan su ne azzalumai.
Sannan ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa wa muminai cewa, idan ya zamanto sun fifita son iyayensu da ‘ya’yansu da ‘yan’uwansu da matansu na aure da sauran danginsu na jini da dukiyoyinsu da suka tara da kasuwancinsu da suke tsoron gurguncewarsa, sun fifita son su a kan son Allah da Manzonsa da jihadi don ɗaukaka kalmar Allah, to su jira har Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo azabarsa ta gaggawa ko mai jinkiri. Allah kuma ba ya shiryar da mutane fasiƙai.

An karɓo daga Anas ɗan Maliku (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ababuwa guda uku duk wanda suka samu tare da shi, to ya samu ɗanɗanon imani: Wanda ya fi son Allah da Manzonsa fiye da komai, kuma ya so mutum don Allah kawai, kuma ya ƙyamaci koma wa kafirci bayan Allah ya kuɓutar da shi, kamar yadda yake ƙin a jefa shi cikin wuta.” [Bukhari #16 da Muslim #43].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ɗayanku ba zai yi imani ba har sai na kasance mafi soyuwa a gare shi fiye da ‘ya’yansa da iyayensa da mutane baki ɗaya.” [Bukhari #15 da Muslim #44].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Hisham (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mun kasance tare da Annabi (ﷺ) yana riƙe da hannun Umaru ɗan Khaɗɗabi (Allah ya ƙara masa yarda) sai ya ce: “Ya Manzon Allah, na fi son ka fiye da komai in ban da raina.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “A’a, na rantse da wanda raina yake a hannunsa, sai ka fi so na fiye da ranka.” Sai Umar ya ce: “To haka ne yanzu. Na rantse da wanda raina yake hannunsa, na fi son ka fiye da raina.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “To yanzu ne ya Umar.” [Bukhari #6632].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗakar da muminai irin tarin falalarsa gare su, ya ba su nasarori daban-daban a yaƙe-yaƙe da dama ba kuwa don yawansu ko ƙarfinsu ba.

2. Jiji-da-kai halaka ce, don haka Allah yake yi mana kashedi da yin sa.

3. Idan Allah ya jarrabi bayinsa har aka yi galaba a kansu, sai su dawo su ƙaskantar da kansu a gabansa su karyo da zukatansu gare shi, da haka sai su cancanci ɗaukaka da samun nasara. Domin nasara tana tattare da ƙaskantar da kai ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. An ware yaƙin ranar Hunaini da ambato saboda ita ce ranar da Musulmi suka tarwatse suka gudu, sannan daga baya suka dawo, Allah kuma ya ɗora su a kan abokan gabansu bayan sun amsa kiran Allah da Manzonsa.

5. Kyautata alaƙa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da mayar da komai hannunsa shi yake sa a samu nasara da ba a iya samun ta ta hanyar yawa ko dukiya ko ‘ya’ya.

Suratut Tauba (25-27)

لَقَدۡ نَصَرَكُمُ ٱللَّهُ فِي مَوَاطِنَ كَثِيرَةٖ وَيَوۡمَ حُنَيۡنٍ إِذۡ أَعۡجَبَتۡكُمۡ كَثۡرَتُكُمۡ فَلَمۡ تُغۡنِ عَنكُمۡ شَيۡـٔٗا وَضَاقَتۡ عَلَيۡكُمُ ٱلۡأَرۡضُ بِمَا رَحُبَتۡ ثُمَّ وَلَّيۡتُم مُّدۡبِرِينَ ٢٥ ثُمَّ أَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَعَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَأَنزَلَ جُنُودٗا لَّمۡ تَرَوۡهَا وَعَذَّبَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۚ وَذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٢٦ ثُمَّ يَتُوبُ ٱللَّهُ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ عَلَىٰ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٧

25. Lalle haƙiƙa Allah Ya taimake ku a wurare da yawa, da kuma ranar (yaƙin) Hunaini lokacin da yawanku ya ruɗe ku sai (yawan naku) bai amfana muku komai ba, ƙasa kuma ta yi muku ƙunci duk da yalwarta, sannan kuka juya kuna masu ba da baya.

26. Sannan Allah Ya saukar wa da Manzonsa da kuma muminai nutsuwarsa, Ya kuma saukar da wasu rundunoni da ba kwa gani, Ya kuma azabtar da waɗanda suka kafirta. Wannan kuwa shi ne sakamakon kafirai.

27. Sannan bayan wannan Allah zai karɓi tuban wanda Ya ga dama. Allah kuwa Mai gafara ne, Mai rahama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da muminai abin da ya faru gare su a ranar yaƙin Hunaini tsakaninsu da ƙabilun Hawazinu da Saƙifu da waɗanda suka goya musu baya, a watan Shawwal na shekara ta takwas bayan hijira. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya taimaki muminai a wuraren yaƙi da yawa, hakanan ya taimake su a ranar yaƙin Hunainu lokacin da yawansu ya ruɗe su, to amma kuma sai yawan bai amfana musu komai ba, ƙasa kuma ta yi musu ƙunci duk kuwa da yalwarta saboda tsananin abin da ya same su; daga bisani suka gudu suna ba wa kafirai baya.
Sai kuma daga baya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da nutsuwarsa da ƙarfin zuciya ga Manzonsa (ﷺ) da muminai, ya kuma saukar da wata runduna ta mala’iku waɗanda babu mai ganin su, ya kuma azabtar da kafirai a wannan rana ta hannun muminai. Wannan kuwa shi ne sakamakon kafirai.
Bayan haka kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna zai karɓi tuban wanda ya ga dama daga cikin waɗannan kafiran, ya shiryar da shi zuwa ga Musulunci. Lalle kuwa Allah mai gafara ne mai jin ƙai.

Hunainu wani kwari ne a tsakanin Makka da Ɗa'ifa. Lokacin da wasu ƙabilu na Larabawa da suke zaune a wannan kwari kamar ƙabilar Hawazinu da Sakifu da Ghaɗafan da sauransu suka sami labarin Annabi (ﷺ) ya ci Makka da yaƙi, sai abin bai yi musu daɗi ba, saboda haka sai suka shirya yaƙar Musulmi, suka fito ƙwansu da kwarkwatarsu da matansu da 'ya'yansu har da dabbobinsu, saboda kada wani daga cikinsu ya yi tunanin gudu ko ja da baya.
Yawancin Musulmi a lokacin ba su da isassun makamai. Musulmi suna shiga cikin wannan kwarin na Hunaini, ba su ankara ba, ashe rundunar Hawazinu waɗanda gwanayen harbi ne sun yi musu kwanton-ɓauna, sai kawai suka far wa Musulmi da harbi da sara da suka, sai Musulmi suka tarwatse, sai aka bar Annabi (ﷺ) da wasu 'yan tsirarun Musulmi tare da shi a tsakiyar kafirai. Da Manzon Allah (ﷺ) ya ga haka sai ya umarci baffansa Abbas wanda yake riƙe da linzamin alfadarar Annabi (ﷺ) ya kirawo Musulmi. Sai Abbas ya kwaɗa musu kira cewa su dawo, sai suka juyo wurin Manzon Allah (ﷺ). Annabi (ﷺ) kuma sai ya zaburi alfadarsa ya nufi kafirai; faɗa ya sake kaurewa tsakanin Musulmi da kafirai; nan ne fa ya damƙi tsakuwoyi da tafukan hannunsa ya watsa wa kafirai a fuska, ya ce: "Ku tarwatse, na rantse da Ubangijin Ka'aba." Daga nan ko sai suka daina gani sosai, suka ɗimauce suka shiga juya baya suna guduwa. Bugu da ƙari kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Musulmi wata runduna ta mala'iku suka taya su yaƙi har nasara ta tabbata gare su. [Dubi, Bukhari #433, 2864, da Muslim #1059,1775, 2865].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hajji ba ta inganta sai daga Musulmi, don haka aka hana kafiri kusantar masallaci mai alfarma.

2. Ba a yarda kafiri ya shiga haramin Makka ba da kowane irin dalili.

3. Abin da ake nufi da 'Masallaci mai alfarma' shi ne haramin Makka baki ɗayansa, domin maganar da aka yi a kan tsoron talauci, saboda ba a ƙwaryar Masallaci ne ake yin kasuwancin ba; ana yin sa ne a duk cikin garin Makka. Kuma da a ce ana nufin hana shigowarsu ƙwaryar Masallaci ne kawai, da ba su ji tsoron talauci ba don wannan. Sun ji tsoron talauci ne don an hana su shigo da duk wani kasuwanci a harami.

4. Hanyar arziƙi ba ɗaya ce ba; hanyoyi ne masu yawa; idan an toshe ɗaya, to wasu masu yawa za su buɗe, saboda falalar Allah tana da yalwa, rahamarsa kuma tana da faɗi, musamman ga wanda zai bar wani abu don Allah, to Allah zai musanya masa da mafi alherin abin da ya bari in ya ga dama.

5. Zafin nema ba ya kawo samu. Arziƙi kuma nufin Allah ne da falalarsa, shi ne mai raba wa mutane arziƙinsu.

Suratut Tauba (28-29)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡمُشۡرِكُونَ نَجَسٞ فَلَا يَقۡرَبُواْ ٱلۡمَسۡجِدَ ٱلۡحَرَامَ بَعۡدَ عَامِهِمۡ هَٰذَاۚ وَإِنۡ خِفۡتُمۡ عَيۡلَةٗ فَسَوۡفَ يُغۡنِيكُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦٓ إِن شَآءَۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٢٨ قَٰتِلُواْ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَلَا بِٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَلَا يُحَرِّمُونَ مَا حَرَّمَ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَلَا يَدِينُونَ دِينَ ٱلۡحَقِّ مِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ حَتَّىٰ يُعۡطُواْ ٱلۡجِزۡيَةَ عَن يَدٖ وَهُمۡ صَٰغِرُونَ ٢٩

28. Ya ku waɗanda suka yi imani, lalle mushrikai najasa ne kawai, saboda haka kada su kusanci Masallaci mai alfarma bayan wannan shekarar tasu. Idan kuma kuna tsoron talauci ne to Allah zai wadata ku daga falalarsa idan Ya ga dama. Lalle Allah Masani ne, Mai hikima.

29. Ku yaƙi waɗanda ba sa yin imani da Allah da ranar lahira, ba kuma sa haramta abin da Allah da Manzonsa suka haramta, kuma ba sa yin addini na gaskiya, daga waɗanda aka bai wa littafi har sai (sun yarda) za su ba da jizya da hannunsu a ƙasƙance.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa, lalle mushirikai najasa ne domin zukatansu cike suke da kafirci da ƙaryatawa, sannan ba sa tsarkake jikinsu daga abin da yake samun su na najasa, don haka kada muminai su ƙara ba su damar shiga masallaci mai alfarma, wato haramin Makka bayan shekara ta tara da yin hijira wadda a cikinta ne Musulmi suka yi watsi da duk wani alƙawari da yake tsakaninsu da mushirikai a baya.
Ya nuna musu cewa, idan suna jin tsoron talauci ne saboda sun hana mushirikai shiga harami da yankewar kasuwanci da su a sanadiyyar haka, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai wadatar da su daga falalarsa idan ya ga dama. Lalle Allah masani ne mai hikima.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su su yaƙi Yahudu da Nasara waɗanda ba sa yin imani da Allah da ranar lahira kuma ba sa haramta abin da Allah da Manzonsa suke haramtawa, ba sa kuma yin addini na gaskiya, wato Musulunci, har sai sun bayar da jiziya da hannunsu a wulaƙance.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda zai ba da labarin wata magana ta kafirci ba za a ɗauka ya yi laifi ba.

2. Duk wanda ya yi wa wani biyayya a kan haramta halal ko halatta haram, to kamar ya ɗauke shi abin bauta ne ba Allah ba.

3. Daga cikin Yahudawa ma akwai masu cewa Allah yana da ɗa, sai dai ‘yan ƙalilan ne ba su da yawa, saboda haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fi jingina wannan mummunar aƙidar ga Nasara.

Suratut Tauba (30-31)

وَقَالَتِ ٱلۡيَهُودُ عُزَيۡرٌ ٱبۡنُ ٱللَّهِ وَقَالَتِ ٱلنَّصَٰرَى ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ ٱللَّهِۖ ذَٰلِكَ قَوۡلُهُم بِأَفۡوَٰهِهِمۡۖ يُضَٰهِـُٔونَ قَوۡلَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَبۡلُۚ قَٰتَلَهُمُ ٱللَّهُۖ أَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ٣٠ ٱتَّخَذُوٓاْ أَحۡبَارَهُمۡ وَرُهۡبَٰنَهُمۡ أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسِيحَ ٱبۡنَ مَرۡيَمَ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُوٓاْ إِلَٰهٗا وَٰحِدٗاۖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ سُبۡحَٰنَهُۥ عَمَّا يُشۡرِكُونَ٣١

30. Yahudawa sun ce: “Uzairu ɗan Allah ne.” Nasara kuma suka ce: “Almasihu ɗan Allah ne.” Wannan faɗarsu ce kawai da bakunansu; suna kwaikwayon faɗar kafiran da suka gabace su ne. Allah Ya tsine musu. Ta ƙaƙa ake kautar da su daga gaskiya?

31. Sun ɗauki malamansu da masu ibadarsu da kuma Almasihu ɗan Maryamu iyayengiji maimakon Allah, alhali kuwa ba abin da aka umarce su sai su bauta wa Abin bauta Ɗaya, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Ya tsarkaka daga abin da suke tara Shi da shi.

A waɗannan ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mummunar aƙidar Yahudawa da Nasara ne ta kiran wasu mutane ‘ya’yan Allah. Yahudawa sun ce, wai Uzairu ɗan Allah ne, Nasara kuwa suka ce Isa Almasihu ɗan Allah ne.
Uzairu, wasu masana sun ce ɗaya ne daga cikin annabawan Banu Isra’ila, wasu kuma sun ce wani babban malami ne a cikinsu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan faɗarsu ce kawai ta fatar baki, suna kwaikwayon maganar kafiran da suka gabace su ne. Allah kuwa ya la'ance su; ta ƙaƙa har ake kautar da su daga kan gaskiya, har su riƙa jingina wa Allah ɗa ba tare da wata hujja ba?

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "A ranar alƙiyama mai shela zai yi shela yana cewa: "Kowace al'umma ta bi abin da take bauta wa." Daga nan ba wani wanda yake bautar wanin Allah kamar masu bautar gumaka face sai sun yi ta aukawa cikin wutar Jahannama. Har ya zama babu sauran kowa sai masu bautar Allah cikin mutanen kirki da ba na kirki ba da sauran ma'abota littafi. Sai a kirawo Yahudawa a ce musu: "Me kuke bauta wa?" Sai su ce: "Mun kasance ne muna bauta wa Uzairu ɗan Allah." Sai a ce musu: "Karya kuke yi, Allah ba ya da mata ba ya da ɗa, to me kuke nema?" Sai su ce: "Kishirwa muke ji ya Ubangijinmu, ka shayar da mu." Sai a nuna su a ce musu: "Ga shi can ba za ku je ku sha ba?" Sai a tattara su a tura su wuta, idan ka gan ta kamar kawalwalniya, sashinta yana rugurguzar sashi, sai su yi ta faɗawa cikinta. Sannan sai a kirawo Nasara, a ce musu: "Me kuke bauta wa?" Sai su ce: "Muna bautar Almasihu ɗan Allah ne." Sai a ce musu: "Karya kuke, Allah ba ya da mata ba ya da ɗa." Sai kuma a ce musu: "To me kuke nema?" Sai su ce: "Kishirwa muke ji ya Ubangijinmu, ka shayar da mu." Sai a nuna musu (wani wuri) a ce: "Ga shi can ba za ku je ku sha ba?" Sai a tattara su zuwa Jahannama kai ka ce kawalwalniya ce sashinta yana rugurguza sashi, sai su yi ta faɗawa cikinta." [Bukhari #4581, da Muslim #183].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, sun mayar da malamansu da masu bauta a cikinsu shugabannin da suke yi wa biyayya ba Allah ba wajen halatta haram da haramta halal. Kuma Nasara sun ɗauki Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a matsayin abin bauta ba Allah ba, alhalin ba a yi musu wani umarni ba sai na su bauta wa abin bauta ɗaya shi ne Allah wanda ba ya da abokin tarayya. Ya tsarkaka kuma ga duk wata shirka da suke yi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah yana yi wa Musulmi albishir har da masu da'awa daga cikinsu cewa, su kwantar da hankalinsu Allah zai ɗaukaka Musulunci ya ba shi rinjaye a bayan ƙasa a kan dukkanin sauran addinai. Kuma wajibi ne Musulmi su yi imani da cewa hakan sai ya faru da ikon Allah.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko Annabi (ﷺ) da shiriya da addinin gaskiya zuwa ga mutane. Ta hanyar shiriya ne ake fahimtar gaskiya, kuma ta hanyar addinin gaskiya ne ake aikata alheri da ayyuka na ƙwarai.

3. Bayanin tsananin gabar ma'abota littafi ga addinin Musulunci addinin gaskiya, ta hanyar jingina masa maganganun ƙarya da zuga mabiyansu a kan yaƙi da shi da yaƙi da Musulmi.

4. Bayanin cewa, babu wata shiriya sai wadda Manzon Allah (ﷺ) ya zo da ita, don haka babu wani addini ko wata ibada da za a karɓa sai in ta dace da abin da Annabi (ﷺ) ya zo da shi.

5. Addini ba zai cika ba har sai an samu ilimi mai amfani da kuma aiki na ƙwarai. Waɗannan su ne shiriya da addini na gaskiya.

يُرِيدُونَ أَن يُطْفِـُٔوا۟ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفْوَٰهِهِمْ وَيَأْبَى ٱللَّهُ إِلَّآ أَن يُتِمَّ نُورَهُۥ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿٣٢﴾ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُشْرِكُونَ ﴿٣٣﴾ يُرِيدُونَ أَن يُطْفِـُٔوا۟ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفْوَٰهِهِمْ وَيَأْبَى ٱللَّهُ إِلَّآ أَن يُتِمَّ نُورَهُۥ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿٣٢﴾ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُشْرِكُونَ ﴿٣٣﴾

32. Suna nufi ne su dushashe hasken Allah da bakunansu, Allah kuwa ba zai ƙyale ba har sai Ya cika haskensa ko da kuwa kafirai sun ƙi.

33. Shi ne wanda Ya aiko Manzonsa da shiriya da kuma addini na gaskiya don Ya ɗora shi a kan dukkanin addinai, ko da kuwa mushrikai sun ƙi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, ma’abota littafi suna ƙoƙarin ɓata addinin Musulunci saboda ƙarerayi da ƙage da suke yi a kansa. To amma duk da haka ba za su yi wata nasara ba, Allah ba zai yarda ba sai ya cika haskensa ya ɗora addininsa a kan sauran addinai ko da kuwa kafirai suna ƙin hakan. Sai kuma ya bayyana cewa, shi ne wanda ya aiko Manzonsa Annabi Muhammadu (ﷺ) da shiriya da addinin gaskiya don ya ɗora shi a kan sauran addinai ko da kuwa mushirikai ba sa so.

An karɓo daga A’isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: “Dare da rana ba za su gushe ba har sai an bauta wa gumakan Lata da Uzza.” Ta ce na ce: “Ya Manzon Allah, ni a da ina zaton cewa yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: “Shi ne wanda ya aiko da Manzonsa da shiriya da kuma addinin gaskiya don ya ɗora shi a kan dukkanin addinai ko da kuwa mushirikai sun ƙi,” na zaci cewa hakan ya cika.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Nan gaba hakan zai kasance lokacin da Allah ya ga dama.” [Muslim #2907].

An karɓo daga Saubanu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah ya tattaro mini duniya wuri guda sai na ga gabashinta da yammacinta, kuma Lalle sai mulkin al’ummata ya kai inda aka tattaro mini daga gare ta.” [Muslim #2889].

An karɓo daga Tamimuddari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle wannan al’amari (Musulunci) sai ya kai duk inda dare da rana suka kai, Allah ba zai bar wani gidan laka ba ko na gashin raƙuma (wato birni da ƙauye) face sai ya shigar da wannan addinin cikinsa, da izzar mai izza ko da ƙaskancin ƙaskantacce, izzar da Allah zai ɗaukaka Musulunci da ita da ƙaskancin da zai ƙaskantar da kafirci da shi.” [Ahmad #16957].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗin Musulmi a kan su guji wasu malamai da wasu masu ibada waɗanda suke karɓar dukiyoyinsu da sunan addini ko ibada, sannan kuma su riƙa ɓatar da su daga hanyar gaskiya suna hana su bin hanyar Allah. Abin da waɗannan malamai da waɗannan masu ibadar suke karɓa a hannun mutane da sunan addini haramun ne suke ci.

2. Malaman da suke karɓar kuɗaɗen jama’a ko masu mulki don su yi musu fatawar da ta saɓa wa shari’a ko su halatta musu haram, ko su halatta musu zalunci da cuta sun shiga cikin wannan ayar ta 34.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci ɓatan ɗan'adam a lamarin dukiyarsa ta ɗaya daga cikin abubuwa biyu:
Na farko, ya kashe dukiyarsa a kan ƙarya da ɓarna, kamar wanda zai kashe dukiyarsa a kan saɓon Allah ko bin son zuciyarsa da ba za ta taimake shi wajen biyayya ga Allah ba.
Na biyu, ya ɓoye dukiyarsa ya ƙi taimaka wa mabuƙata ko wajen addinin Allah.

4. Gargaɗin muminai da su guji halayyar masu tara dukiyar da ba za ta amfana musu komai ba sai dai ta jefa su cikin fitina da tsananin son tara abin duniya.

5. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya soki wanda ya nemi dukiya da gumin goshinsa ko ya gaje ta amma kuma ya ɓoye ya ƙi fitar da haƙƙinta, to lalle wanda ya tattara dukiyar al'umma ya ɓoye ya ƙi fito da ita ga masu haƙƙi a cikinta, wannan shi ne ya fi cancantar azaba mai raɗaɗi.

6. Duk wanda ya so wani abu, ya fifita shi a kan ɗa'ar Allah, to da shi za a yi masa azaba ranar alƙiyama.

Suratut Tauba (34-35)

*يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلۡأَحۡبَارِ وَٱلرُّهۡبَانِ لَيَأۡكُلُونَ أَمۡوَٰلَ ٱلنَّاسِ بِٱلۡبَٰطِلِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۗ وَٱلَّذِينَ يَكۡنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلۡفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٖ ٣٤ يَوۡمَ يُحۡمَىٰ عَلَيۡهَا فِي نَارِ جَهَنَّمَ فَتُكۡوَىٰ بِهَا جِبَاهُهُمۡ وَجُنُوبُهُمۡ وَظُهُورُهُمۡۖ هَٰذَا مَا كَنَزۡتُمۡ لِأَنفُسِكُمۡ فَذُوقُواْ مَا كُنتُمۡ تَكۡنِزُونَ ٣٥

34. Ya ku waɗanda suka yi imani, lalle da yawa daga malaman (Yahudawa) da masu ibada (Nasara) tabbas suna cin dukiyoyin mutane ta hanyar cuta, suna kuma toshe hanyar Allah. Waɗanda kuma suke ɓoye zinariya da azurfa ba sa ciyar da ita saboda Allah, to ka yi musu albishir da wata azaba mai raɗaɗi.

35. Ranar da za a narkar da su (zinariya da azurfa) cikin wutar Jahannama sannan a yi wa fuskokinsu da kuyaɓunsu da bayansu lalas da su, (a ce da su): "Wannan shi ne abin da kuka taskace wa kanku, sai ku ɗanɗani abin da kuka kasance kuna taskacewa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin wani mugun hali na manyan malaman Yahudawa da masu ibada a cikin Nasara, watau yadda suke cin dukiyoyin mutane ta hanyar ƙarya da ɓarna, suke take gaskiya suna hana mutane karɓar ta.
Sai kuma ya bayyana cewa, waɗanda suke tara zinariya da azurfa su ɓoye ba sa fitar musu da haƙƙin Allah, ba sa ciyar da su don taimakon addinin Allah, ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi wa irin waɗannan mutane albishir da wata azaba mai raɗaɗi, a ranar da za a narka wannan dukiyar tasu da wutar Jahannama, a yi musu lalas da ita a goshinsu da geffansu da bayansu, sannan ana faɗa musu maganar ɓacin rai, ana cewa: Wannan shi ne abin da kuka tara kuka kuma ɓoye domin kawunanku, don haka sai ku ɗanɗani sakamakon abin da kuka tara a ɓoye.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani ma'abocin zinare ko azurfa wanda ba ya fitar da zakka, face sai ya kasance a ranar alƙiyama an mayar masa su wata shimfiɗa ta wuta, a narka su a wutar Jahannama, sai a yi ta yi masa lalas da su a kwiɓinsa da goshinsa da bayansa. Duk sa'adda suka yi sanyi sai a sake ɗawo masa da su yadda suke, haka za a yi ta yi masa a cikin wani yini wanda gwargwadonsa shekara dubu hamsin ne, har sai an gama yin hukunci tsakanin bayi, sannan za a nuna masa hanyarsa, ko zuwa Aljanna ko kuma zuwa wuta." [Muslim #987].

An karɓo daga Khalid ɗan Aslam ya ce: Mun fita tare da Abdullahi ɗan Umar (Allah ya kara masa yarda), sai wani baƙauye ya yi masa tambaya game da wannan ayar. Sai Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce masa: “Duk wanda ya tara wannan dukiyar ya ɓoye ya hana zakkarta, to bone ya tabbata gare shi. Wannan ayar ta sauka kafin a saukar da hukuncin zakka ne. To bayan an saukar da hukuncin zakka sai Allah ya sauya zakka ta zamanto tsarkakewa ce ga dukiya.” [Bukhari #1504].

Wato Abdullahi ɗan Umar yana nufin wannan hukuncin ya kasance ne a farkon Musulunci kafin a farlanta zakka: Duk wani wanda yake da dukiya da ta fi ƙarfin buƙatarsa, to bai halatta a gare shi ya ɓoye ta ya ƙi taimaka wa mabuƙata da ita ba. Daga bisani aka farlanta zakka sai aka shafe wannan hukunci. [Dubi, Ibn Hajar, *Fathul Bari*, Juzu’i na 3]. Amma yawanci malaman tafsiri sun tafi ne a kan cewa, tana nufin mutanen da suke tara dukiya su ɓoye ba sa fitar mata da zakka.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Na rantse da Ubangijin Ka’aba su ne mafiya asara.” Sai Abu Zarrin ya tambaye shi: “Na ba da mahaifina da mahaifiyata fansa a gare ka, su wane ne waɗannan?” Sai ya ce: “Su ne masu yawan dukiya, sai dai wanda ya bayar da dukiyarsa nan da can da can, watau ta gabansa da bayansa da damansa da hagunsa; waɗannan kuwa ‘yan kaɗan ne. Babu wani mai raƙuma ko shanu ko ƙananan dabbobi sannan ba ya fitar musu da zakka face sai sun zo a ranar gobe ƙiyama da girma da ƙiba fiye da yadda suke a duniya, suna tunkuyin sa da ƙahonninsu, suna taka shi da kofatansu, duk sa’adda na ƙarshe suka ƙare sai na farko su kuma dawo musu, haka za a yi ta yi masa har sai an yi hukunci a tsakanin mutane.” [Bukhari #6638, da Muslim #990].

An karɓo daga Ummu Salamah (Allah ya ƙara masa yarda) ta ce: “Na kasance nakan sanya kayan kwalliya na zinariya, sai na ce wa Manzon Allah (ﷺ): “Shin shi ma yana daga cikin ɓoyayyiyar dukiya?” Sai ya ce: “Matuƙar ya isa zakka, kuma aka cire masa, to ba ya daga cikin taskakakkiyar dukiya.” [Abu Dawud #1564, da Ɗabarani, *Almu’ujamul Kabir*, Juzu’i na 23, Shafi na 281, hadisi na 613].

An karɓo daga Sauban (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da wannan ayar ta sauka, sai suka ce: “To wace dukiya za mu riƙe?” Sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Ni zan nemo muku ilimi a kan haka.” Sai ya hau raƙuminsa ya isa wajen Annabi (ﷺ) ni kuma ina bin sa a baya, sai ya ce: “Ya Manzon Allah, wacce dukiya za mu riƙa?” Sai ya ce: “Ɗayanku ya riƙi zuciya mai godiya da harshe mai ambaton Allah da mata mumina wadda za ta taimaka masa a kan al’amarin lahira.” [Tirmizi #3094, da Ibn Maja #1856, da Ahmad #22437].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kiyaye lokaci da kula da shi wani babban jigo ne a cikin tsarin ginin nagartacciyar al’umma da nesanta ta da ayyukan ta-ci-barkatai marasa tsari.

2. Girmama aikata zalunci a cikin watanni masu alfarma wani abu ne mai cike da maslaha ga al’umma, domin ƙaurace wa zalunci da miyagun ayyuka a cikinsu zai taimaka wajen rage ɓarna ko magance ta gaba ɗaya.

3. Yana daga cikin hukuncin shari’a duk wata ibada da take da alaƙa da watanni ko shekara to ana lissafinta ne da watanni na ƙamariyya, wato hudowar wata da cikarsa, kamar azumin watan Ramadana da aikin hajji da hukunce-hukuncen iddar mata da takaba da shayarwa da makamantansu.

4. Canza shari’ar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai canza asalinta ba. Asalinta yana nan yadda yake da farko, canjin kuwa ɓata ne.

5. Kafirci yana ƙaruwa kamar yadda imani yake ƙaruwa.

6. Saɓon Allah duk da cewa ba a ninninka samakonsa, to amma zai iya girmama saboda girman darajar wuri ko lokacin da aka yi shi a ciki.

7. Yana daga cikin mafi munin ayyuka halatta abin da Allah ya haramta ko haramta abin da ya halatta.

Suratut Tauba (36-37)

إِنَّ عِدَّةَ ٱلشُّهُورِ عِندَ ٱللَّهِ ٱثۡنَا عَشَرَ شَهۡرٗا فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِ يَوۡمَ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ مِنۡهَآ أَرۡبَعَةٌ حُرُمٞۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُۚ فَلَا تَظۡلِمُواْ فِيهِنَّ أَنفُسَكُمۡۚ وَقَٰتِلُواْ ٱلۡمُشۡرِكِينَ كَآفَّةٗ كَمَا يُقَٰتِلُونَكُمۡ كَآفَّةٗۚ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلۡمُتَّقِينَ ٣٦ إِنَّمَا ٱلنَّسِيٓءُ زِيَادَةٞ فِي ٱلۡكُفۡرِۖ يُضَلُّ بِهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُحِلُّونَهُۥ عَامٗا وَيُحَرِّمُونَهُۥ عَامٗا لِّيُوَاطِـُٔواْ عِدَّةَ مَا حَرَّمَ ٱللَّهُ فَيُحِلُّواْ مَا حَرَّمَ ٱللَّهُۚ زُيِّنَ لَهُمۡ سُوٓءُ أَعۡمَٰلِهِمۡۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٣٧

36. Lalle adadin watanni a wurin Allah wata goma sha biyu ne a cikin littafin Allah, tun ranar da Ya halicci sammai da ƙasa, daga cikinsu akwai (wata) huɗu masu alfarma. Wannan shi ne addini madaidaici. To kada ku zalunci kanku a cikinsu, kuma ku yaƙi mushrikai gaba ɗaya kamar yadda suke yaƙar ku gaba ɗaya. Ku kuma sani cewa Allah Yana tare da masu taƙawa.

37. Lalle jinkiri ba wani abu ba ne ban da ƙari cikin kafirci, wanda da shi (jinkirin) ake ɓatar da waɗanda suka kafirta, suna halatta shi a wata shekarar, su kuma haramta shi a wata, wai don su daidaita adadin abin da Allah Ya haramta, sai su halatta abin da Allah Ya haramta. An ƙawata musu munanan ayyukansu. Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, adadin watanni a wurinsa wata goma sha biyu ne, haka ya hukunta kuma ya ƙaddara a cikin Lauhul Mahfuz tun lokacin da ya halicci sammai da ƙasa. Daga cikinsu akwai wata huɗu masu alfarma da ya haramta yin yaƙi a cikinsu, su ne Rajab da Zulƙi'ida da Zulhijja da Muharram.

An karɓo daga Abu Bakrata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle zamani ya juyo kamar siffarsa yadda yake ranar da Allah ya halicci sammai da ƙasa: Shekara wata goma sha biyu ne, daga cikinsu akwai huɗu masu alfarma, uku a jere su ne Zulƙa'ada da Zulhijja da Muharram, sai kuma watan Rajab, watan ƙabilar Mudhar wanda yake a tsakanin watan Jumada da watan Sha'aban." [Bukhari #7447, da Muslim #1679].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan shi ne addinin gaskiya shi ne kuma lissafi na daidai, don haka ya yi umarni da kada su zalunci kawunansu a cikin waɗannan watanni ta hanyar shiga yaƙi ko aikata miyagun laifuffuka. Sai kuma ya umarci muminai da su yaƙi mushirikai gaba ɗayansu kamar yadda su ma suke yaƙar su gaba ɗaya, kuma su sani Allah yana tare da masu taƙawa, watau masu kiyaye dokokinsa.
Sannan kuma ya yi bayanin cewa, abin da Larabawa mushirikai suke yi na jinkirta watanni masu alfarma da canza shari'ar Allah a kansu, wannan wani ƙari ne a cikin kafircinsu. Watau sai su halatta yin yaƙi a watan Muharram a wata shekarar watau su canza shi da watan Safar maimakon watan Muharram. Bayan shekara ta zagayo sai su dawo da haramcin watan Muharram kamar yadda yake, wai don su

daidaita abin da Allah ya haramta musu kowace shekara ba daɗi ba ragi a lissafi, wato watannin haramci sun cika huɗu cif-cif, to amma an jinkirta watan Muharram ya koma Safar, don haka sun halatta abin da Allah ya haramta, an ƙawata musu munanan ayyukansu. Allah kuwa ba ya shiryar da mutane kafirai masu kafewa a kan miyagun aƙidu da munanan ayyuka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi da sukan waɗanda suke zama a gida ba sa fita yaƙi tare da Manzon Allah (ﷺ) saboda tsananin son duniya da jin daɗinta.

2. Gwargwadon yadda bawa yake kwaɗayin duniya haka noƙewarsa ga ayyukan alheri take kasancewa.

3. Jin daɗin duniya ba komai ne ba idan aka kwatanta shi da na lahira.

4. Duk abin da ɗan'adam yake aikatawa ba zai cuci Allah da komai ba; sakamakon wannan abin yana komawa ne gare shi, idan alheri ya aikata ya ga alheri idan kuma sharri ya aikata to shi zai gani.

5. Duk wanda Allah yake tare da shi da buwayarsa da ƙarfinsa da rahamarsa, to wannan bai dace a ce ya gamu da wata damuwa ko tsoro ba.

6. Darasi ga masu da'awa da kira zuwa ga gaskiya su yi haƙuri da abin da zai same su na wahala da jarraba da tsangwamar maƙiya.

7. Samun nutsuwa wata ni'ima ce daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) musamman a lokacin tashin hankali da abubuwan ban tsoro.

8. Duk wanda aikinsa ya yi daidai da na Annabi (ﷺ) ya saba wa waninsa, to wannan mutumin yana cikin waɗanda suka bi Annabi (ﷺ), don haka yana da rabo daga faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): "Kada ka damu, haƙiƙa Allah yana tare da mu."

Suratut Tauba (38-40)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَا لَكُمۡ إِذَا قِيلَ لَكُمُ ٱنفِرُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ ٱثَّاقَلۡتُمۡ إِلَى ٱلۡأَرۡضِۚ أَرَضِيتُم بِٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا مِنَ ٱلۡأٓخِرَةِۚ فَمَا مَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا فِي ٱلۡأٓخِرَةِ إِلَّا قَلِيلٌ ٣٨ إِلَّا تَنفِرُواْ يُعَذِّبۡكُمۡ عَذَابًا أَلِيمٗا وَيَسۡتَبۡدِلۡ قَوۡمًا غَيۡرَكُمۡ وَلَا تَضُرُّوهُ شَيۡـٔٗاۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ٣٩ إِلَّا تَنصُرُوهُ فَقَدۡ نَصَرَهُ ٱللَّهُ إِذۡ أَخۡرَجَهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ثَانِيَ ٱثۡنَيۡنِ إِذۡ هُمَا فِي ٱلۡغَارِ إِذۡ يَقُولُ لِصَٰحِبِهِۦ لَا تَحۡزَنۡ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَنَاۖ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ عَلَيۡهِ وَأَيَّدَهُۥ بِجُنُودٖ لَّمۡ تَرَوۡهَا وَجَعَلَ كَلِمَةَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلسُّفۡلَىٰۗ وَكَلِمَةُ ٱللَّهِ هِيَ ٱلۡعُلۡيَاۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ٤٠

38. Ya ku waɗanda suka yi imani, me ya same ku ne idan aka ce da ku ku fita yaƙi saboda Allah sai ku yi nauyin jiki? Yanzu kun zaɓi rayuwar duniya a kan ta lahira? Ai jin daɗin rayuwar duniya abu ne ƙanƙani dangane da na lahira.

39. Idan ba za ku fita (yaƙi ba to (Allah) zai azabtar da ku da azaba mai raɗaɗi, Ya kuma canja wasu mutanen daban, ba kuwa za ku cutar da Shi da komai ba. Allah kuwa Mai iko ne a kan komai.

40. Idan ba ku taimake shi ba (watau Manzon Allah) to haƙiƙa Allah Ya taimake shi lokacin da kafirai suka fitar da shi (daga Makka), alhalin suna su biyu, lokacin da suke a cikin kogo, yayin da yake ce wa abokinsa (Abubakar): “Kada ka damu, lalle Allah yana tare da mu,” sai Allah Ya saukar masa da nutsuwarsa Ya kuma ƙarfafe shi da runduna wadda ba ku gan ta ba, Ya kuma sanya kalmar waɗanda suka kafirta ta zama ƙaskantacciya. Kalmar Allah kuwa ita ce maɗaukakiya. Allah kuma Mabuwayi ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙara zaburar da muminai da su tashi su yi jihadi don Allah su daina nauyin jiki, ya kirawo su da sunan ‘imani’, yana faɗa musu cewa, me ya sa idan aka kirawo su su fito domin tafiya yaƙin ɗaukaka addinin Allah sai su riƙa nauyin jiki su fifita zaman gida da more rayuwar duniya a kan ta lahira da ni’imar cikinta? Jin daɗin duniya ƙanƙani ne dangane da na lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsorata su da cewa idan ba su fita jihadi ba, to zai yi musu azaba mai tsanani, ya kuma musanya su da wasu mutane daban waɗanda idan an kira su zuwa jihadi su amsa a guje, kuma ba za su cutar da Allah da komai ba don sun ƙi amsa kiransa. Kuma Allah mai iko ne a kan komai.
Sai kuma ya ci gaba da cewa, idan sun ƙi taimakon Annabi (ﷺ) to ai Allah zai taimake shi kamar yadda ya taimake shi a baya lokacin da kafiran Kuraishawa suka fitar da shi daga ƙasar haihuwarsa Makka, a lokacin da suke su biyu, ba kowa tare da shi sai Abubakar As-Siddiƙ (Allah ya kara masa yarda), lokacin da suka shiga kogon dutsen *Sauru* don ƃoye wa abokan gaba masu neman su ruwa-a-jallo. A lokacin ne yake lallashin Abubakar yana ce masa, kada ya yi baƙin ciki, Allah yana tare da su. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da nutsuwarsa ga Manzonsa (ﷺ) ya kuma ƙarfafe shi da rundunar mala’iku waɗanda ba wanda ya gan su, Allah kuma ya mayar da kalmar kafirai ta zama a ƙasa; kalmar Allah kuwa ita ce a sama. Allah kuma mabuwayi ne gwani mai hikima, saboda haka yana da ikon azabta kafirai ya karya ƙadarinsu, don ko babu abin da ya fi ƙarfinsa, mai hikima ne cikin dukkan ayyukansa da maganganunsa.
Bayan kafiran Kuraishawa sun addabi Annabi (ﷺ) da tsangwama da wulaƙanci har ta kai sun shirya kashe shi, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya yi hijira tare da sahabbansa zuwa garin Madina. Sahabban Annabi (ﷺ) ne suka fara yin hijira zuwa can, sannan daga baya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da yin hijira tare da Sahabinsa kuma babban amininsa Abubakar (Allah ya kara masa yarda). Bayan sun fita daga garin Makka sai suka fara fakewa a kogon wani dutse da ake kiran sa Dutsen *Sauru*. Da aka wayi gari Kuraishawa ba su ga Annabi (ﷺ) da Abubakar ba sai suka fita suka bazama neman su. Suka iso dab da wannan kogon suka tsaya. Sayyidina Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya tsorata ƙwarai ya kiɗime hankalinsa ya tashi, yana zaton ko za su iya ganin su, har ya ce: “Wallahi da abin a ce ɗayansu zai duba ƙarƙashin ƙafarsa ne to da Lalle ya gan mu.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce da shi: “Kada ka damu, haƙiƙa Allah yana tare da mu.... Me kake tsammanin kuwa zai samu mutum biyu da Allah ne na ukunsu?” [Dubi, Bukhari #4663, da Muslim #2381].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan ana buƙatar mayaka don kare Musulunci da ƙasar Musulmi, to fita yaƙi ya zama wajibi a kan kowa da kowa, musamman yayin da kafirai suka kawo wa Musulmi farmaki.

2. Kamar yadda jihadi da kai yake zama wajibi idan an samu tsananin buƙata, to haka ma jihadi da dukiya yake wajibi.

3. Wanda ba zai iya yin jihadi da jikinsa ba saboda wata larura, to amma yana da wadatar dukiya, to wajibi ne a kansa ya yi da dukiyarsa.

4. Jihadi da kai ya ƙunshi jihadi da harshe da hannu. Wani lokaci jihadi da harshe ma ya fi ƙarfi da tasiri, kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) yake cewa: “Ku yaƙi mushirikai da hannayenku da harsunanku da kuma dukiyoyinku.” [Abu Dawud #2504, da Nasa’i #3096, da Ahmad #12268] daga Anas.

5. Son a samu ganimar duniya cikin sauƙi ɗabi’a ce ta ɗan’adam, musamman ma ga wanda bai yi imani da ranar lahira ba.

6. Yin rantsuwar ƙarya da gangan yakan kai mutum ga halaka.

7. Annabi (ﷺ) yakan yi ijtihadi cikin abin da ba a saukar masa da wahayi a kansa ba, yakan kuma dace ko ya kuskure, to amma ba a ƙyale shi bisa kuskure, nan da nan ake faɗakar da shi.

Suratut Tauba (41-43)

ٱنفِرُواْ خِفَافٗا وَثِقَالٗا وَجَٰهِدُواْ بِأَمۡوَٰلِكُمۡ وَأَنفُسِكُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٤١ لَوۡ كَانَ عَرَضٗا قَرِيبٗا وَسَفَرٗا قَاصِدٗا لَّٱتَّبَعُوكَ وَلَٰكِنۢ بَعُدَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلشُّقَّةُۚ وَسَيَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ لَوِ ٱسۡتَطَعۡنَا لَخَرَجۡنَا مَعَكُمۡ يُهۡلِكُونَ أَنفُسَهُمۡ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ إِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ٤٢ عَفَا ٱللَّهُ عَنكَ لِمَ أَذِنتَ لَهُمۡ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَكَ ٱلَّذِينَ صَدَقُواْ وَتَعۡلَمَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٤٣

41. Ku fita yaƙi kuna da kuzari ko ba ku da shi, ku kuma yi yaƙi da dukiyoyinku da kawunanku saboda Allah. Wannan ya fi alheri a gare ku, in kun kasance kun san (haka).

42. Da (abin da za su samu) amfani ne na kusa, ko tafiya gajeriya, to lalle da sun bi ka, sai dai kuma tafiyar ta yi musu tsawo; kuma za su zo suna rantsuwa da Allah cewa: “Da mun sami hali da lalle mun fita tare da ku”, suna hallaka kansu ne kawai, Allah kuwa Yana sane da cewa lalle su tabbas maƙaryata ne.

43. Allah Ya yafe maka; don me ka yi musu izini? Ai har sai ka gane musu gaskiya ka kuma san maƙaryata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da su yi gaggawar fita yaƙi don Allah, suna cikin kuzari ko ba sa ciki, kuma su yi jihadi da dukiyoyinsu da kawunansu don su ɗaukaka kalmar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), saboda yin haka shi ne alheri gare su in sun san hakan.

An karɓo daga Ubadatu ɗan Samitu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ku yi jihadi don Allah, domin jihadi don Allah wata ƙofa ce daga cikin ƙofofin Aljanna, da shi ne Allah yake raba mutum da damuwa ko baƙin ciki.” [Ahmad #22699].

An karɓo daga Sahlu ɗan Sa’adu As-Sa’idi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Yin dako (ribaɗi) na rana ɗaya don Allah ya fi duniya da abin da yake cikinta. Wurin ajiyar bulalar ɗayanku a Aljanna ya fi duniya da abin da yake cikinta. Fitar maraice da bawa zai yi don Allah ko sammako don Allah ya fi duniya da abin da yake cikinta.” [Bukhari #2892, da Muslim #1881].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, da a ce abin da yake kiran munafukai zuwa gare shi wata ganima ce da ke kusa mai sauƙin samuwa ko wata tafiya marar wahala to da sun fita tare da shi. To amma sai ya zamanto tafiyar mai tsawo ce, domin tafiya ce daga

Madina da nufin yaƙi da Rumawa, don haka sai waɗannan munafukai suka noƙe suka ƙi bin Annabi (ﷺ). Sannan Allah ya faɗa masa cewa, bayan sun je sun dawo munafukan za su zo suna ta rantsuwa da Allah cewa, da sun sami hali da sun fita tare da Manzon Allah (ﷺ); suna hallaka kansu da gangan alhali suna sane. Allah ya san cewa, haƙiƙa maganar da suke faɗa ƙarya suke yi.
Wasu munafukai kuma kamar su Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salulu da Aljaddu ɗan Kaisu da Rifa'atu ɗan Tabutu, su kimanin mutum talatin da tara, sun zo wurin Annabi (ﷺ) suka gabatar masa da uzurinsu na cewa ba za su iya fita yaƙin Tabuka ba, suka shirya masa ƙarerayi, Annabi kuma ya karɓi uzuransu ya musu izini su yi zamansu a gidajensu. To shi ne sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɓe shi game da wannan cikin ruwan sanyi, ya ce ya yi masa afuwa, don me ya yi musu izini su zauna gidajensu kada su bi shi yaƙi? Ya dace a ce kada ya yi musu izini har sai ya gane masu gaskiya a cikinsu ya kuma gane maƙaryata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muminai masu imani da Allah da ranar lahira ba sa neman abin da za su fake da shi su ƙi yin aikin da Allah ya umarce su da shi.

2. Marar cikakken imani a zuciyarsa shi ne wanda ba ya jin son aikata wani alheri.

3. Hanyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a sarari take, kuma bayyananna ce ga duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, saboda haka ba ya kai-kawo wajen bin ta.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna kishinsa ga Annabi (ﷺ) da sahabbai sai ya hana munafukai fita yaƙi tare da su, don gudun kada su haifar musu da matsala ta hanyar ruɗani da gulma a tsakaninsu.

5. Samuwar munafukai a tsakiyar al'umma suna kai-kawo a tsakaninsu wani babban dalili ne da zai hana cin nasara ga wannan al'umma.

6. Munafukai ba muminai ne ba.

7. Mai shakka a zuciyarsa ba mumini ne ba.

Suratut Tauba (44-47)

لَا يَسۡتَ ٔۡذِنُكَ ٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ أَن يُجَٰهِدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِٱلۡمُتَّقِينَ ٤٤ إِنَّمَا يَسۡتَ ٔۡذِنُكَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَٱرۡتَابَتۡ قُلُوبُهُمۡ فَهُمۡ فِي رَيۡبِهِمۡ يَتَرَدَّدُونَ ٤٥ ۞وَلَوۡ أَرَادُواْ ٱلۡخُرُوجَ لَأَعَدُّواْ لَهُۥ عُدَّةٗ وَلَٰكِن كَرِهَ ٱللَّهُ ٱنۢبِعَاثَهُمۡ فَثَبَّطَهُمۡ وَقِيلَ ٱقۡعُدُواْ مَعَ ٱلۡقَٰعِدِينَ ٤٦ لَوۡ خَرَجُواْ فِيكُم مَّا زَادُوكُمۡ إِلَّا خَبَالٗا وَلَأَوۡضَعُواْ خِلَٰلَكُمۡ يَبۡغُونَكُمُ ٱلۡفِتۡنَةَ وَفِيكُمۡ سَمَّٰعُونَ لَهُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ ٤٧

44. Waɗanda suka yi imani da Allah da ranar lahira ba sa neman izininka don kada su yi yaƙi da dukiyoyinsu da kawunansu. Allah kuwa yana sane da masu taƙawa.

45. Waɗanda kawai suke neman izininka su ne waɗanda ba sa imani da Allah da ranar lahira, zukatansu kuma suka yi kokwanto, saboda haka suke ta dawurwuri a cikin kokwantonsu.

46. Da kuwa sun yi niyyar fita to da sun yi masa tanadi, sai dai kuma Allah Ya ƙi zaburar da su, sai Ya dankwafar da su, aka kuma ce (da su): “Ku zauna tare da mazauna (gida).”

47. Da sun fito cikinku ɗin, to ba abin da za su ƙare ku da shi sai taɓarɓarewa, kuma lalle da sun yi ta shige da fice a tsakaninku suna ƙoƙarin haifar muku da fitina, a cikinku kuma akwai masu jiyo musu (wato abokan gaba) magana. Allah kuwa Masanin azzalumai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, babu yadda za a yi muminan da suka yi imani da Allah da ranar lahira su riƙa neman izini a wajensa na ya amince musu su ƙi fita yaƙi su yi zamansu a gidajensu, saboda su mutane ne masu kiyaye dokokin Allah, Allah kuwa yana sane da su.
Ya bayyana cewa, masu neman izinin a ba su dama su ƙi fita yaƙi su ne munafukai masu kawo uzurori na ƙarya, domin ba su yi imani da Allah da ranar lahira ba, zukatansu suna cike da shakku, don haka suna cikin wannan shakkun nasu suna ta dawurwuri, su ba su tsaya a kan imani ba su kuma ba su koma cikin kafirci gaba ɗaya ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Misalin munafuki kamar misalin akuya ce mai kai-komo tsakanin garke biyu na dabbobi, wani lokaci ta bi waɗannan, wani lokaci kuma ta bi waɗancan.” [Muslim #2784].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da a ce waɗannan munafukai sun yi niyyar fita yaƙin da sun yi tanadi dominsa, sai dai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙi zaburar da su tare da muminai, sai ya daɗa danƙwafar da su ya saka musu mutuwar jiki da kasala, kuma aka ce da su su zauna tare da mazauna gida, wato mata da yara da marasa lafiya da masu larura waɗanda ba za su iya fita yaƙi ba.
Sai kuma aka bayyana illar da fitarsu za ta haifar da cewa, da a ce ma za su fita tare da muminai to babu abin da za su ƙara musu sai sharri da ɓarna da ruɗani a tsakaninsu, sannan kuma ko shakka babu da sun yi ta shige-da-fice a tsakanin muminai suna yaɗa gulma da ƙiyayya a cikinsu, wanda yin hakan zai iya yin mummunar illa a cikin muminai, saboda a cikinsu akwai waɗanda sun yarda da su. Allah kuma yana sane da azzalumai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Makircin kafirai ba zai yi wani tasiri wajen kawar da gaskiya ba, duk kuwa irin yadda za su matsa lamba wajen shirya sharri da mugun nufi, Allah zai mayar musu da mugun nufinsu a kansu.

2. Duk wanda ya zaɓi ya saɓa wa Allah don cim ma wata manufa, to Allah zai lalata masa wannan buƙatar tasa, kamar yadda waɗannan munafukan suka ƙi fita jihadi tare da muminai wai don guje wa fitina, Allah ya bayyana cewa da ma sun faɗa cikin fitinar tsundum.

3. Karantar da muminai a kan cewa, kada su bari baƙin cikin wata musifa da ta same su ya raunana musu zuciya har abokan gabarsu su sami ƙarfin cin nasara a kansu, lalle su yarda da ƙaddarar Allah, su sani Allah mai taimakon su ne kuma mai taimakon addininsa.

4. Allah ne majiɓincin lamarin muminai, duk kuwa wanda Allah ya zamanto shi ne majiɓincin lamarinsa, to lalle ba zai taɓa tozarta shi ba har abada.

5. Wanda ya fita jihadi don Allah ba zai taɓa yin asara ba, domin dole ne ya samu ɗayan abubuwa biyu: Imma dai ya ci nasara, ko kuma a kashe shi ya yi shahada, kowane ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa biyu kuwa riba ce.

6. Munafukai ba sa dogaro ga Allah, don haka koyaushe al’amuransu a lalace suke.

Suratut Tauba (48-52)

لَقَدِ ٱبۡتَغَوُاْ ٱلۡفِتۡنَةَ مِن قَبۡلُ وَقَلَّبُواْ لَكَ ٱلۡأُمُورَ حَتَّىٰ جَآءَ ٱلۡحَقُّ وَظَهَرَ أَمۡرُ ٱللَّهِ وَهُمۡ كَٰرِهُونَ ٤٨ وَمِنۡهُم مَّن يَقُولُ ٱئۡذَن لِّي وَلَا تَفۡتِنِّيٓۚ أَلَا فِي ٱلۡفِتۡنَةِ سَقَطُواْۗ وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمُحِيطَةُۢ بِٱلۡكَٰفِرِينَ ٤٩ إِن تُصِبۡكَ حَسَنَةٞ تَسُؤۡهُمۡۖ وَإِن تُصِبۡكَ مُصِيبَةٞ يَقُولُواْ قَدۡ أَخَذۡنَآ أَمۡرَنَا مِن قَبۡلُ وَيَتَوَلَّواْ وَّهُمۡ فَرِحُونَ ٥٠ قُل لَّن يُصِيبَنَآ إِلَّا مَا كَتَبَ ٱللَّهُ لَنَا هُوَ مَوۡلَىٰنَاۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٥١ قُلۡ هَلۡ تَرَبَّصُونَ بِنَآ إِلَّآ إِحۡدَى ٱلۡحُسۡنَيَيۡنِۖ وَنَحۡنُ نَتَرَبَّصُ بِكُمۡ أَن يُصِيبَكُمُ ٱللَّهُ بِعَذَابٖ مِّنۡ عِندِهِۦٓ أَوۡ بِأَيۡدِينَاۖ فَتَرَبَّصُوٓاْ إِنَّا مَعَكُم مُّتَرَبِّصُونَ ٥٢

48. Haƙiƙa tun da can sun nemi yaɗa fitina, suka hargitsa maka al’amari, har sai da gaskiya ta zo, al’amarin Allah kuma ya bayyana, su kuwa suna masu ƙin (haka).

49. Daga cikinsu kuma akwai wanda yake cewa: “Ka yi mani izinin (zama), kada ka jefa ni cikin fitina.” Tabbas, ai cikin fitinar suka faɗa. Lalle Jahannama kuwa mai kewaye kafirai ce.

50. Idan wani alheri ya same ka sai ya baƙanta musu rai; idan kuwa musiba ce ta same ka sai su riƙa cewa: “Haƙiƙa mu da ma tuni mun ɗauki matakin kauce mata,” sai kuma su juya baya suna masu farin ciki.

51. Ka ce: “Ba abin da zai same mu sai abin da Allah Ya rubuta mana, shi ne Majiɓincin al’amuranmu; kuma ga Allah kaɗai muminai sai su dogara.”

52. Ka ce: “Shin akwai abin da kuke jira ya same mu in ban da ɗayan kyawawan abubuwa biyu (wato nasara ko shahada). Mu kuwa muna jiran (mu ga) Allah Ya aukar muku da wata azaba daga wurinsa ko kuwa ta hannunmu? To sai ku jira, lalle mu ma masu jira ne tare da ku.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana fallasa munafukai ne da cewa tun da can sun nemi yaɗa fitina da yamutsi a tsakanin Musulmi, sun yi nufin sharri ga Annabi (ﷺ) suka yi ta tunani iri-iri da ƙulle-ƙulle daban-daban don su cim ma burinsu, har sai da nasarar Allah ta zo addinin Musulunci ya yi galaba ba tare da suna son hakan ba.
Munafukai a baya can kamar lokacin yaƙin Uhudu sun yi ƙoƙarin haddasa yamutsi tsakanin Musulmi da kawo musu rabuwar kai lokacin da Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salulu ya sulale da wani kaso na rundunar Musulmi, don ya haddasa rauni a rundunar Musulmi, kafirai su yi galaba a kansu, amma bai yi nasara ba. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a cikin munafukai akwai wanda yake faɗa wa Annabi cewa, shi a ba shi izini ya zauna kada a fita yaƙar Rumawa da shi, wai don kada a jefa shi cikin fitinar kallon matan Rumawa, wai shi ba zai iya ganin su ya yi haƙuri ba tare da ya neme su ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ai lalle waɗannan sun riga sun faɗa cikin wata babbar fitina, saboda sun yarda su ci gaba da zama a cikin kafirci da guje wa fita jihadi tare da Manzon Allah (ﷺ) da saɓa masa, kuma lalle Jahannama a kewaye take da kafirai.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa Aljaddu ɗan Kaisu: “Shin za ka fita yaƙar Rumawa?” Sai Jaddu ya ce: “Ko za ka yi min izinin in yi zamana ya Manzon Allah, saboda ni mutum ne mai sha’awar mata, kuma ina jin tsoron kada in ga matan Rumawa in faɗa cikin fitina.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ɗauke masa kai ya ce masa: “Je ka na yi maka izini.” Sai

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar. [Dubi, Ibn Abi Hatim, *Tafsir*, Juzi'i na 6, Shafi na 1809].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, idan muminai suka fita yaƙi, suka kuma ci nasara a kan kafirai suka samo ganimar yaƙi, rayuwarsu ta ƙara yalwa, wannan zai baƙanta wa munafukai sosai, za su ji haushin faruwar haka ga muminai. Amma kuma da musifa ce ta kisa ko rauni za ta samu Musulmi, ko a yi nasara a kansu, to da za ka gan su suna cewa, ai su da man sun riga sun ɗauki matakin kare kansu, sun yi taka-tsantsan don haka abin da ya samu Musulmi su bai same su ba, saboda haka sai su juya su tafi suna farin ciki. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa musu cewa, babu wata musiba da za ta same shi, shi da sahabbansa sai dai abin da Allah ya riga ya rubuta musu, domin shi ne majiɓincin al'amarinsu mai taimakon su a koyaushe, don haka muminai su dogara ga Allah shi kaɗai, su fawwala masa al'amuransu.
Hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya faɗawa munafukai cewa abin da suke jira ya sami muminai bai wuce ɗayan abubuwa biyu kyawawa ba, wato samun nasara a kan maƙiya ko kuma mutuwar shahada. Amma su muminai suna jiran Allah ya saukar wa da munafukai azaba daga wurinsa ko kuma ta hannunsu. Don haka su yi ta jira su ma muminai suna nan suna jira tare da su.

An karɓo daga Suhaibu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Al'amarin mumini yana da ban mamaki, domin duk al'amuransa alheri ne, babu mai samun haka kuwa sai mumini. Idan abin farin ciki ya same shi sai ya yi godiya sai wannan ya zame masa alheri; idan kuma wata cuta ta same shi sai ya yi haƙuri, wannan ma sai ya zame masa alheri." [Muslim #2999].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Allah ya rubuta abubuwan da ya ƙaddara wa halittunsa kafin ya halicci sammai da ƙasa da shekara dubu ɗari biyar." [Muslim #2653].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ruhin ɗa'a shi ne mutum ya gabatar da ita da niyyar bautar Allah da sallama masa; duk wanda ya yi ɗa'a ba da wannan manufar ba to ya yi aikin banza.

2. Ya kamata ga Musulmi idan zai tashi salla ya tashi da karsashi da nishaɗi da walwala, zuciyarsa tana cike da farin ciki; kada ya kwaikwayi munafukai ya riƙa jin damuwa a ransa yayin da ya tashi yin ta.

3. Hakanan lokacin da Musulmi yake fitar da zakkar dukiyarsa, ya riƙa jin farin ciki a zuciyarsa.

4. Munafukai duk da suna salla suna sadaka, to amma a haƙiƙa su kafirai ne domin sun kafirce wa Allah da Manzonsa, kuma sallarsu da sadakarsu ba don Allah suke yin ta ba.

5. Ayyukan kafiri ba sa samun karɓuwa wajen Allah saboda kafircinsa.

Suratut Tauba (53-54)

قُلْ أَنفِقُواْ طَوْعًا أَوْ كَرْهًا لَّن يُتَقَبَّلَ مِنكُمْ إِنَّكُمْ كُنتُمْ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ﴿٥٣﴾ وَمَا مَنَعَهُمْ أَن تُقْبَلَ مِنْهُمْ نَفَقَٰتُهُمْ إِلَّآ أَنَّهُمْ كَفَرُواْ بِٱللَّهِ وَبِرَسُولِهِۦ وَلَا يَأْتُونَ ٱلصَّلَوٰةَ إِلَّا وَهُمْ كُسَالَىٰ وَلَا يُنفِقُونَ إِلَّا وَهُمْ كَٰرِهُونَ ﴿٥٤﴾

53. Ka ce: “Ku ciyar (da dukiyarku) cikin daɗin rai ko a bisa dole (duka ɗai suke), ba za a karɓa muku ba; don kuwa lalle kun kasance ku mutane ne fasiƙai.

54. Ba kuwa abin da ya hana a karɓi ciyarwar tasu sai don sun kafirce wa Allah da Manzonsa, ba sa kuma zuwa salla sai suna cikin kasala, ba kuma sa ciyarwa sai ala tilas.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya bayyana wa munafukai cewa, duk ɗaya ne a gare shi ko su yarda su ciyar da dukiyarsu ko kada su yarda, Allah dai ba zai taɓa karɓar sadakarsu ba saboda sun tabbata su mutane ne fasiƙai. Kuma ba wani abu ya jawo aka ƙi karɓar sadakarsu ba sai don sun kafirce wa Allah da Manzonsa; idan ma sun tashi za su yi salla sai su tashi cikin kasala da nauyin jiki, kuma duk wani aikin alheri da za a zo da shi ba za su taimaka da dukiyarsu ba sai da ɓacin rai, suna yi amma ba da son ransu ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bai dace mumini ya riƙa kallon rayuwar holewa da kafirai suke ciki ba yana sha’awar irinta.

2. Tarin dukiya da ‘ya’ya da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ba wa maƙiyansa a duniya ƙarin azaba ce da talala yake yi musu, ba alama ce ta ƙauna ba.

3. Munafukai ba sa cikin sahabban Annabi (ﷺ). Wato a cikin sahabbai kakaf babu munafuki.

4. Munafukai a ɗabi’arsu matsorata ne, don haka samuwarsu a cikin rundunar Musulmi ba za su ƙare su da komai ba sai matsala.

Suratut Tauba (55-57)

فَلَا تُعۡجِبۡكَ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُمۡۚ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُعَذِّبَهُم بِهَا فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَتَزۡهَقَ أَنفُسُهُمۡ وَهُمۡ كَٰفِرُونَ ٥٥ وَيَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ إِنَّهُمۡ لَمِنكُمۡ وَمَا هُم مِّنكُمۡ وَلَٰكِنَّهُمۡ قَوۡمٞ يَفۡرَقُونَ ٥٦ لَوۡ يَجِدُونَ مَلۡجَا أَوۡ مَغَٰرَٰتٍ أَوۡ مُدَّخَلٗا لَّوَلَّوۡاْ إِلَيۡهِ وَهُمۡ يَجۡمَحُونَ ٥٧

55. To kada dukiyoyinsu da ‘ya’yansu su ƙayatar da kai. Allah Yana nufin kawai Ya azabta su ne da su a rayuwar duniya, rayukansu kuma su zazzago a halin suna kafirai.

56. Sukan kuma rantse da Allah cewa lalle suna tare da ku, alhali kuwa ba sa tare da ku, kawai dai su wasu mutane ne matsorata.

57. Da za su sami wata mafaka ko wani kogo ko wata mashiga, to da sun juya zuwa gare shi suna gaggawar (shiga).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin halayen munafukai, tare da hana Annabi (ﷺ) ya yi sha’awar dukiyoyinsu da ‘ya’yansu, ya bayyana masa cewa ya ba su su ne ba don komai ba sai don ya yi musu azaba da su a duniya, ta hanyar su yi ta yi musu wahala da bauta da ɗawainiyar kula da su, sannan kuma idan sun zo mutuwa su mutu kafirai.An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk wanda yake lahira ce abin damuwarsa, to Allah zai ba shi wadatar zuci, ya tattaro masa jama’arsa wuri guda, duniya kuma ta zo masa a wulaƙance. Wanda kuwa duniya ce abin damuwarsa, sai Allah ya sanya masa talaucinsa a gaban idanunsa (watau ya

jefa masa tsoron talauci a zuciyarsa), ya tarwatsa masa jama'arsa, kuma ba abin da zai samu a duniya sai iya abin da aka ƙaddara masa." [Ibn Maja #4105, da Ibn Hibban #680].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ba da labari cewa, munafukai maƙaryatan gaske ne sannan ga su da tsoro, don haka suke yawan rantse wa muminai cewa suna tare da su, amma alal haƙiƙa ba sa cikinsu, sai dai kawai suna jin tsoron muminai ne shi ya sa suke rantsuwar cewa suna cikinsu don su sami aminci da zaman lafiya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa da munafukan nan za su sami wani wuri da za su fake a ciki su kare kansu ko wani kogo ko wani rami a ƙasa to da sun gudu can sun ɓoye saboda tsananin ƙiyayyar da suke yi wa Musulmi da ƙoƙarin guje wa fita yaƙi tare da Annabi (ﷺ).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda ya nemi duniya ita kaɗai, to a lamarin addini zai tuƙe ga munafunci. Amma wanda ya nemi ta gwargwadon yadda Allah ya halatta masa, kuma manufarsa ga neman ta ta zama ita ce cim ma wasu maslahohi na addini, to wannan ce hanyar gaskiya kuma dukiyarsa za ta amfane shi duniya da lahira.

2. Wajibi ne ga mumini ya riƙa gamsuwa da abin da Allah ya ba shi, ya ƙwallafa zuciyarsa wajen neman duniya ga Allah shi kaɗai.

3. Bai dace ga bawa ya zama yardarsa da rashin yardarsa suna da alaƙa ne kawai da son zuciyarsa da buƙatarsa ta duniya ba.

4. Duk waɗanda alaƙarsu da wani shugaba sun gina ta ne a kan abin duniya kawai, idan sun samu su yabe shi, idan ya hana su su zage shi, to waɗannan sun ɗauki mugun hali ne na munafunci.

5. Ana bayar da zakka ne kawai ga waɗannan da Allah ya ambata, don haka bai dace a shigar da dukiyar zakka a cikin wasu ayyuka na al'umma ba kamar gina masallatai ko makarantu ko rijiyoyi da makamantansu.

Suratut Tauba (58-60)

وَمِنْهُم مَّن يَلْمِزُكَ فِي ٱلصَّدَقَٰتِ فَإِنْ أُعْطُواْ مِنْهَا رَضُواْ وَإِن لَّمْ يُعْطَوْاْ مِنْهَآ إِذَا هُمْ يَسْخَطُونَ ﴿٥٨﴾ وَلَوْ أَنَّهُمْ رَضُواْ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَقَالُواْ حَسْبُنَا ٱللَّهُ سَيُؤْتِينَا ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ وَرَسُولُهُۥٓ إِنَّآ إِلَى ٱللَّهِ رَٰغِبُونَ ﴿٥٩﴾ ۞ إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلْفُقَرَآءِ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَٱلْعَٰمِلِينَ عَلَيْهَا وَٱلْمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمْ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَٱلْغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِ ۖ فَرِيضَةً مِّنَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٦٠﴾

58. Daga cikinsu kuma akwai waɗanda suke aibata ka game da rabon sadaka; idan an ba su wani abu daga cikinta to sai su gamsu, idan kuwa ba a ba su daga cikinta ba sai ka gan su suna fushi.

59. Da kuwa za su yarda da abin da Allah da Manzonsa suka ba su, su kuma ce: "Allah ya ishe mu, kuma Allah zai ba mu daga falalarsa Manzonsa ma (zai ba mu), lalle mu masu kwaɗayi ne a wurin Allah kaɗai."

60. Dukiyoyin zakka na matalauta ne kaɗai da miskinai da ma'aikatanta da waɗanda ake lallashin zukatansu da kuma game da 'yanta bayi da waɗanda ake bi bashi da kuma wajen jihadi saboda Allah da matafiyi. Farilla ce daga Allah. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da fayyace miyagun halayen munafukai ne, waɗanda suka haɗa da sukan Manzon Allah (ﷺ) game da rabon dukiyar zakka; idan an ba su yadda ransu yake so sai su karɓa su gamsu da rabon ba tare da wani ƙorafi ba, amma idan ba a ba su yadda suke so ba, to sai su yi fushi, su riƙa wasu ƙananan maganganu.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Muna tare da Annabi (ﷺ) yana rabon sadaka, sai wani mutum mai suna Zul Khuwaisira ya zo wajensa ya ce: "Ya Manzon Allah, ka yi adalci." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Kaiconka! Wane ne zai yi adalci idan ni ban yi ba? Ka halaka, ka yi hasara idan har ban yi adalci ba…" [Dubi Bukhari #6933 da Muslim #1065].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da a ce waɗannan munafukan sun gamsu da abin da Allah ya ba su, kuma Annabi (ﷺ) ya raba musu, suka ce Allah ya ishe su, kuma Allah zai yi musu baiwa da falalarsa, Annabi (ﷺ) kuma zai raba musu, kuma wurin Allah kaɗai suke kwaɗayi, to da hakan ya fi zame musu alheri a duniyarsu da addininsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin waɗanda suka cancanci a ba su dukiyar zakka kamar haka:

1. Faƙirai: Su ne waɗanda ba su mallaki abin da za su yi rabin shekara suna ci ba.

2. Miskinai: Su ne waɗanda ba su mallaki abin da za su shekara suna ci ba.
A wurin wasu malamai miskinai sun fi faƙirai tsananin buƙata.

3. Ma'aikatan zakkar: Su ne waɗanda suke tattara zakka su kula da ita har a raba wa waɗanda suka cancanta. Waɗannan ma ana ba su ladansu daga dukiyar zakka ko da kuwa su mawadata ne.

4. Waɗanda ake lallashin zukatansu: Su ne kafiran da ake ƙoƙarin jawo hankalinsu zuwa ga Musulunci, da waɗanda ba su daɗe da karɓar Musulunci ba, imaninsu bai yi ƙarfi ba. Su ma ana ba su zakka don a nuna musu cewa Musulunci addini ne mai tausayi da jin ƙai.

5. 'Yanta bayi: Su ne bayin da aka ɗora musu fansa, sai a taimaka masa da abin da zai fanshi kansa da shi; ko kuma a fanshi Musulmin da ya faɗa hannun maƙiya suka riƙe shi fursunan yaƙi; ko a sayi bawa a 'yanta shi.

6. Masu bashi a kansu: Su ne waɗanda suka ci bashi suka kasa biya, ko wanda ya ɗauki bashin wani don tabbatar da sulhu tsakanin masu husuma. Waɗannan ma ana ba su daga cikin dukiyar zakka don su warware bashin da ke kansu.

7. A wajen jihadi don ɗaukaka addinin Allah: Ana amfani da dukiyar zakka wajen shirya rundunar masu jihadi da sayen makamai da ababen hawa don fita yaƙi da guzirin mayaƙan.

8. Matafiyi: Shi ne matafiyin da guzurinsa ya ƙare bai kai garinsa ba. Ana taimaka masa daga cikin dukiyar zakka da gwargwadon abin da zai ƙarasa da shi garinsu.
Waɗannan su kaɗai ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yarda a ba su dukiyar zakka. Zakka wata farilla ce daga Allah, Allah kuwa masani ne mai hikima.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ba mai yawo yana roƙon mutane ne miskini ba, wanda idan aka ba shi loma ɗaya ko biyu, ko dabino ɗaya ko biyu an sallame shi ba; miskini shi ne wanda ba ya samun abin da zai ishe shi, ba a san ma da shi ba balle har a

ba shi sadaka, shi kuma ba ya miƙewa tsaye cikin mutane ya roƙe su.” [Bukhari #1479, da Muslim #1039].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Zakka ba ta halatta ga mai wadata ba, ko mutum ƙaƙƙarfa lafiyayye.” [Ahmad #9061, da Nasa’i #2597, da Ibn Maja #1839].

An karɓo daga Ubaidullahi ɗan Adiyyu ɗan Khiyar ya ce: Wasu mutane su biyu sun ba shi labarin cewa, sun je wajen Manzon Allah (ﷺ) suka roƙe shi ya ba su zakka, sai ya ɗaga kansa ya ɗube su da kyau, ya gan su ƙarfafa ne sai ya ce: “In kuna so in ba ku, amma ku sani cewa mawadaci da ƙaƙƙarfan da zai iya yin sana’a ba su da rabo a cikinta.” [Ahmad #17972, da Abu Dawud #1633, da Nasa’i #2598].

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) ya aiko da dukiyar zinare daga Yaman zuwa ga Manzon Allah (ﷺ) sai Annabi (ﷺ) ya raba ta ga mutum huɗu, su ne: Al-Aƙara’u ɗan Habisu Al-Hanzali da Uyainatu ɗan Badr Al-Fazari da Alƙamatu ɗan Ulasatu Al-Amiri da Zaidul Khairi Aɗɗa’i. Sai Kuraishawa suka yi fushi suka ce: “Yanzu yaya za ka ba shugabannin Najadu mu kuma ka bar mu hakanan?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle ni na yi haka ne don lallashin su.” [Bukhari #7432, da Muslim #1064].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cutar da Annabi (ﷺ) ta hanyar sukan sa da aibata shi kafirci ne, kuma duk wanda ya aikata hakan ya cancanci azaba mai raɗaɗi duniya da lahira.

2. Yana daga cikin al’adar munafukai yawan rantsuwa ko da ba a nemi hakan daga wajensu ba, saboda sun tabbatar da cewa su maƙaryata ne, don haka suke yawan rantsuwa don su kawar da zargin da ake yi musu na yin ƙarya da yaudara.

3. Yardar Allah da ta Manzonsa ita ce gaba a wurin duk wani mumini.

4. Duk wanda yake saɓa wa Allah da Manzonsa da gangan to ya san da sanin cewa ya cancanci tozarta mai girma a ranar gobe ƙiyama idan bai tuba ba.

5. Haƙƙin Allah yana tare da haƙƙin Manzonsa (ﷺ), don haka duk wanda ya cuci Manzon Allah (ﷺ) to Allah ya cuta, kamar yadda wanda ya bi Manzon Allah to ya bi Allah.

Suratut Tauba (61-63)

وَمِنْهُمُ ٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ ٱلنَّبِيَّ وَيَقُولُونَ هُوَ أُذُنٌۚ قُلْ أُذُنُ خَيْرٍ لَّكُمْ يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ وَيُؤْمِنُ لِلْمُؤْمِنِينَ وَرَحْمَةٌ لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمْۚ وَٱلَّذِينَ يُؤْذُونَ رَسُولَ ٱللَّهِ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٦١﴾ يَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ لَكُمْ لِيُرْضُوكُمْ وَٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ أَحَقُّ أَن يُرْضُوهُ إِن كَانُواْ مُؤْمِنِينَ ﴿٦٢﴾ أَلَمْ يَعْلَمُوٓاْ أَنَّهُۥ مَن يُحَادِدِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَأَنَّ لَهُۥ نَارَ جَهَنَّمَ خَٰلِدًا فِيهَاۚ ذَٰلِكَ ٱلْخِزْيُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٦٣﴾

61. Daga cikinsu kuma akwai waɗanda suke cutar Annabi suna kuma cewa: “Shi mai saurare ne kawai.” Ka ce (da su: Shi) “Mai sauraren alheri ne dominku; yana imani da Allah, yana kuma gaskata muminai, kuma rahama ne ga waɗanda suka yi imani daga cikinku.” Waɗanda kuwa suke cutar Manzon Allah suna da azaba mai raɗaɗi.

62. Suna rantse muku da Allah don su samu yardarku, Allah da Manzonsa kuwa su suka fi cancanta su yardar da su in sun kasance muminai.

63. Yanzu ba su sani ba cewa, wanda yake jayayya da Allah da Manzonsa, to lalle yana da wutar Jahannama da zai dawwama a cikinta? Wannan kuwa kunyata ce mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da fallasa munafukai ne ta hanyar bayanin wasu miyagun ɗabi'unsu, yana cewa daga cikinsu akwai masu cutar da Annabi (ﷺ) suna cewa, wai shi mai ɗaukan maganganu ne kawai yana yarda da su ba tare da ya tantance gaskiyarsu da rashinta ba. Don haka suke ganin idan sun je sun rantse masa sun faɗa masa kowace irin ƙarya yana yarda da su ya karɓi hanzarinsu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya mayar musu da martani cewa, ai shi mai sauraren alheri ne ba sharri ba; idan ya samu wani mummunan labari a kansu ba ya kama su da shi saboda yawan haƙurinsa, don haka yake sauraron hanzarinsu yana karɓa saboda kyawawan ɗabi'unsa. Yana yin imani da Allah yana kuma gaskata abin da muminai suke faɗa masa, amma ba abin da ya ji daga bakin kafirai ko munafukai ba, kuma shi rahama ne ga muminai masu gaskiya. Amma munafukai masu cutar da shi (ﷺ) to suna da azaba mai raɗaɗi a duniya da lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, munafukai suna rantse wa muminai da Allah don su sami yardarsu da amincewarsu, ya nuna cewa Allah ne da Manzonsa ya fi cancanta su nemi yardarsu idan har da gaske su muminai ne kamar yadda suke nunawa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Manzon Allah (ﷺ) yana zaune a inuwar ɗaya daga cikin ɗakunansa tare da wasu Musulmi, har ma inuwar ta kusa janyewa gaba ɗaya, sai ya ce: "Yanzu za ku ga wani mutum zai zo yana kallon ku da idanun Shaiɗan, idan ya zo muku kada kowa ya yi masa magana." Sai ga wani mutum mai jajayen idanuwa ya zo. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya kirawo shi ya ce masa: "Me ya sa kai da wane da wane kuke zagi na?" Annabi (ﷺ) ya ambaci sunayensu. Sai wannan mutumin ya tafi ya kirawo su, suka zo suka dinga yi wa Manzon Allah rantsuwa da Allah cewa ba haka ne ba, suka gabatar da hanzarinsu, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "Sai su rantse masa (da Allah) kamar yadda suke rantse muku, suna kuma zaton cewa a kan wani abu suke…." [Ahmad #2407, da Al-Hakim #3795].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba yi wa waɗannan munafukai kashedi da cewa, ba su san duk wanda ya saɓa wa Allah da Manzonsa yake kuma gaba da su ba cewa, yana da sakamakon wutar Jahannama wadda zai dawwama a cikinta har abada, kuma wannan ita ce kunyata mai girma?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya ƙullaci wani mugun nufi a zuciyarsa na cutar da Musulmi da Musulunci, to sai Allah ya tona masa asiri, kuma ya yi masa matsananciyar uƙuba.

2. Izgili ga addini ta kowane hali kafirci ne.

3. Duk girman zunubi idan bawa ya tuba to Allah yana karɓar tubansa.

يَحۡذَرُ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ أَن تُنَزَّلَ عَلَيۡهِمۡ سُورَةٞ تُنَبِّئُهُم بِمَا فِي قُلُوبِهِمۡۚ قُلِ ٱسۡتَهۡزِءُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ مُخۡرِجٞ مَّا تَحۡذَرُونَ ٦٤ وَلَئِن سَأَلۡتَهُمۡ لَيَقُولُنَّ إِنَّمَا كُنَّا نَخُوضُ وَنَلۡعَبُۚ قُلۡ أَبِٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ وَرَسُولِهِۦ كُنتُمۡ تَسۡتَهۡزِءُونَ ٦٥ لَا تَعۡتَذِرُواْ قَدۡ كَفَرۡتُم بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡۚ إِن نَّعۡفُ عَن طَآئِفَةٖ مِّنكُمۡ نُعَذِّبۡ طَآئِفَةَۢ بِأَنَّهُمۡ كَانُواْ مُجۡرِمِينَ ٦٦

64. Munafukai suna tsoron a saukar musu da wata sura mai ba su labarin abin da yake cikin zukatansu. Ka ce : “Ku yi ta izgili, lalle Allah Mai bayyana abin da kuke tsoron (bayyanarsa) ne.”

65. Kuma lalle idan har ka tambaye su, tabbas za su ce: “Kawai muna kutse ne da wasa.” To ka ce (da su): “Yanzu Allah ne da ayoyinsa da Manzonsa kuka kasance kuna yi wa izgili?”

66. Kada ku kawo wani uziri, haƙiƙa kun dai kafirta bayan imaninku. Idan Muka yafe wa wata ƙungiya daga cikinku to za Mu azabtar da wata ƙungiyar saboda kuwa sun kasance masu laifi ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da bankaɗo wasu miyagun halaye ne na munafukai, inda ya bayyana cewa su koyaushe a tsorace suke suna fargabar kada wata sura ta Alƙur’ani ta sauko wadda za ta bayyana abin da suka ɓoye na munafinci da kafirci a zukatansu, sai Allah ya umarci Annabinsa (ﷺ) da ya faɗa musu cewa, su ci gaba da yin izgilin da suke yi kar su fasa, to amma su sani cewa lalle sai Allah ya fallasa abin da suke jin tsoron bayyanarsa ga muminai.
Sai ya bayyana cewa, idan Annabi (ﷺ) ya tambayi munafukai game da irin miyagun maganganun da suke yi na sukansa shi da sahabbansa da addinin Musulunci, to za su haƙiƙance a kan cewa su fa ba da gaske suke yi ba, su kawai kutse ne da wasa suke yi. Sai Allah ya umarci Annabi ya ƙalubalance su da cewa, yanzu Allah da ayoyinsa da Manzonsa suka mayar ababen wasa da izgili? To su daina kawo wani hanzari, domin sun kafirta bayan imaninsu. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa wasu daga cikinsu afuwa saboda sun tuba har a zuci ya karɓi tubansu, to amma zai yi wa wasu daga cikinsu azaba saboda sun tabbata masu laifi ne.

An karɓo daga Abdullah ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “A lokacin yaƙin Tabuka, wata rana ana zaune sai wani mutum ya buɗi baki ya ce: “Ban taba ganin mutane haɗamammu masu yawan ƙarya matsorata a wurin yaƙi irin waɗannan alarammomin namu ba?” (Yana nufin sahabban Annabi (ﷺ)). Sai wani mutum a majalisin ya ce masa: “Karya kake, kai dai kawai mutum ne munafuki, kuma tabbas sai na faɗa wa Manzon Allah abin da ka faɗa (ﷺ).” Sai labari ya iske Annabi (ﷺ) kuma Alƙur’ani ya sauko.” Abdullahi ɗan Umar ya ce: “Na ga wannan mutumin riƙe da igiyar sirdin taguwar Manzon Allah (ﷺ) yana bin Manzon Allah yana tuntuɓe da duwatsu yana cewa: “Ya Manzon Allah, kutse ne kawai da wasa muke yi.” Manzon Allah (ﷺ) yana ce masa: “Yanzu da Allah ne da ayoyinsa da Manzonsa kuke yi wa izgili?” [Ibn Jarir, *Tafsir* #16912, da Ibn Abi Hatim, Juzu’i na 6 Shafi na 1830].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin cewa halayyar munafukai mazansu da matansu a kowane zamani da kowane wuri iri ɗaya ce.

2. Ɓarna a addini ko dai ta kasance mummunar aƙida ce da furta miyagun maganganu wannan shi ne kutse; ko kuma ta hanyar aiki da saɓanin gaskiya, wannan kuwa shi ne more rayuwa. Na farko su ne bidi’o’i, na biyu kuwa shi ne bin son zuciya. Waɗannan kuwa su ne tushen duk wani sharri da bala’i a addini da rayuwa.

3. Wanda duk ya manta da Allah, to Allah ya yi masa alƙawarin uƙuba iri biyu, watau zai yi watsi da shi, kuma zai mantar da shi kansa, wato ya kasa gane duk wata maslaharsa da za ta amfane shi.

4. Mutane masu ji da ƙarfinsu ko tarin dukiya da ‘ya’ya sukan makance su kasa tuna Allah wanda shi ne ya yi musu wannan ni’imar, su kuma kasa tuna yadda Allah ya saukar da azabarsa ga waɗansu mutane a baya waɗanda sun fi su komai yayin da suka bijire wa koyarwar annabawansu.

5. Soyayyar munafukai a fatar baki take ba ta je zuciya ba. Suna iya haɗa kansu don yaƙar gaskiya, amma kowa da son zuciyarsa da ta saɓa da ta ɗan’uwansa, saɓanin muminai waɗanda Allah ya haɗa zukatansu gaba ɗaya a kan gaskiya da taimakon juna ko da kuwa sun saba ta fuskar ƙabila da ƙasa da launin fata da yare.

6. Gargaɗi da tsawatarwa a kan koyi da kafirai game da abin da suka keɓanta da shi, ko yake a matsayin alamar addininsu da aƙidarsu.

Suratut Tauba (67-70)

ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلْمُنَٰفِقَٰتُ بَعْضُهُم مِّنۢ بَعْضٍۚ يَأْمُرُونَ بِٱلْمُنكَرِ وَيَنْهَوْنَ عَنِ ٱلْمَعْرُوفِ وَيَقْبِضُونَ أَيْدِيَهُمْۚ نَسُوا۟ ٱللَّهَ فَنَسِيَهُمْۚ إِنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ هُمُ ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿٦٧﴾ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلْمُنَٰفِقِينَ وَٱلْمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلْكُفَّارَ نَارَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ هِىَ حَسْبُهُمْۚ وَلَعَنَهُمُ ٱللَّهُۖ وَلَهُمْ عَذَابٌ مُّقِيمٌ ﴿٦٨﴾ كَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ كَانُوٓا۟ أَشَدَّ مِنكُمْ قُوَّةً وَأَكْثَرَ أَمْوَٰلًا وَأَوْلَٰدًا فَٱسْتَمْتَعُوا۟ بِخَلَٰقِهِمْ فَٱسْتَمْتَعْتُم بِخَلَٰقِكُمْ كَمَا ٱسْتَمْتَعَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُم بِخَلَٰقِهِمْ وَخُضْتُمْ كَٱلَّذِى خَاضُوٓا۟ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ حَبِطَتْ أَعْمَٰلُهُمْ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿٦٩﴾ أَلَمْ يَأْتِهِمْ نَبَؤُا۟ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ قَوْمِ نُوحٍ وَعَادٍ وَثَمُودَ وَقَوْمِ إِبْرَٰهِيمَ وَأَصْحَٰبِ مَدْيَنَ وَٱلْمُؤْتَفِكَٰتِۚ أَتَتْهُمْ رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظْلِمَهُمْ وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿٧٠﴾

67. Munafukai maza da munafukai mata sun yi kama da juna (wajen munafunci). Suna umurni da mummunan aiki suna kuma hana kyakkyawan aiki, kuma suna damƙe hannayensu (wajen yin alheri); sun manta da Allah, sai Shi ma Ya yi watsi da su. Lalle munafikai su ne fasiƙai.

68. Allah kuwa Ya yi wa munafukai maza da mata da kuma kafirai alƙawarin wutar Jahannama wadda za su dawwama a cikinta. Ita ta ishe su. Allah kuma Ya tsine musu, suna kuma da azaba mai ɗorewa.

69. (Kun yi) kama da waɗanda suke gabaninku; sun fi ku ƙarfi da yawan dukiyoyi da kuma ’ya’ya; sai suka more rabonsu (na duniya), to ku ma sai kuka more da naku rabon, kamar yadda waɗanda suke gabaninku suka more da irin nasu rabon, kuka kuma kutsa (cikin ɓarna) kamar yadda suka kutsa. Waɗannan, ayyukansu sun ruguje a duniya da lahira. Waɗannan kuwa su ne hasararru.

70. Yanzu labarin waɗanda suke gabaninsu bai zo musu ba: Mutanen (Annabi) Nuhu da Adawa da Samudawa, da mutanen (Annabi) Ibrahimu da kuma mutanen Madyana da waɗanda aka kifar (watau mutanen Annabi Luɗu)? Manzanninsu sun zo musu da (ayoyi) mabayyana; ba kuma zai zamana Allah Ya zalunce su ba sai dai kawunansu ne kawai suke zalunta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da labarta wa muminai wani abin kunyar daban na munafukai, da cewa, munafukai mazansu da matansu halinsu guda ne, ɗabi’arsu ta munafunci iri ɗaya ce, suna umarni da mummunan aiki suna kuma hana kyakkyawan aiki, sannan suna damƙe

hannayensu wajen yin alheri, ba sa bayar da abin da ya wajaba su bayar daga dukiyoyinsu, sun kuma manta da ambaton Allah, sai su ma Allah ya yi watsi da su, ya ƙi shiryar da su, ya ƙi yi musu rahama, to kuma haka zai bar su a wutar Jahannama su dawwama cikin azaba har abada.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi wa munafukai maza da mata narko na wutar Jahannama wadda za su shige ta su zauna cikinta har abada. Ta ishe su uƙuba. Allah kuma ya nisanta su daga rahamarsa, suna da wata azaba ta har abada wadda babu ƙaƙƙautawa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fuskantar da maganarsa ga munafukai da kafirai ya faɗa musu cewa, suna yin irin ayyukan al'ummomin da suka gabace su, waɗanda kuma sun fi su ƙarfi da tarin dukiya da yawan 'ya'ya, don haka suka more rabonsu na jin daɗin duniya, suka fifita shi a kan ni'imar lahira. To su ma munafukai haka suka more rabonsu na jin daɗin duniya suka bijire wa lahira kamar yadda kafiran da suka gabace su suka yi, kuma suka kutsa cikin irin abin da kafiran suka kutsa cikinsa. To waɗannan ayyukansu gaba ɗaya sun rushe a duniya da lahira, kuma su ne hasararru.
Har wa yau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fuskantar da tambayarsa ga mushirikai da kafirai cewa, ba su samu labarin yadda Allah ya hallaka al'ummomin da suka shuɗe ba; watau mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanen Madyana, wato mutanen Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda Allah ya kifar da ƙasarsu, ya mayar da samanta ta koma ƙasa? Duk waɗannan al'ummomi manzanninsu sun je musu da mu'ujizoji bayyanannu, to amma sai suka ƙaryata su. A kan haka sai Allah ya hallakar da su, kuma Allah ba zai taɓa zaluntar su ya yi musu azabar da ba su cancanta ba, sai dai kawunansu kawai suka riƙa zalunta ta hanyar kafirce wa Allah da saɓa wa manzanninsa, don haka suka cancanci Allah ya halaka su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mumini masoyin ɗan'uwansa mumini ne, mai taimakon sa ne ko da kuwa gari ko ƙabila ba su haɗa su ba.

2. Siffofin muminai sun yi hannun riga da siffofin munafuki.

3. Yaɗa alheri da kawar da sharri da mugun abu yana buƙatar haɗin kan muminai da taimakekeniya a tsakaninsu.

4. Muminai za su shiga Aljanna ne da rahamar Allah ba da ayyukansu ba duk nagartarsu.

5. Umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna yana daga cikin abin da yake bambance tsakanin mumini da munafuki.

6. Muminai maza da mata duka sakamakonsu a Aljanna daidai-wa-daida ne, saboda dukkansu sun yi tarayya wajen aiki na ƙwarai da barin mummunan aiki.

7. Yardar Allah ga bawansa ta zarce ni'imar gidan Aljanna, domin yardar Allah siffarsa ce, Aljanna kuwa halittarsa ce.

وَٱلْمُؤْمِنُونَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتُ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٍ ۚ يَأْمُرُونَ بِٱلْمَعْرُوفِ وَيَنْهَوْنَ عَنِ ٱلْمُنكَرِ وَيُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَيُطِيعُونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ سَيَرْحَمُهُمُ ٱللَّهُ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٧١﴾ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَمَسَٰكِنَ طَيِّبَةً فِى جَنَّٰتِ عَدْنٍ ۚ وَرِضْوَٰنٌ مِّنَ ٱللَّهِ أَكْبَرُ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٧٢﴾

71. Muminai maza da muninai mata kuwa masoyan juna ne: Suna yin umurni da kyakkyawa abu suna kuma hana mummunan, suna kuma tsai da salla suna ba da zakka suna kuma bin Allah da Manzonsa. Waɗannan Allah zai yi musu rahama. Lalle Allah kuwa Mabuwayi ne Mai hikima.

72. Allah Ya yi wa muninai maza da muminai mata alƙawarin gidajen Aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu suna masu dawwama a cikinsu, da kuma wuraren zama masu kyau a cikin gidajen Aljanna na dawwama. Yardar Allah kuwa ita ce fiye da komai. Wannan shi ne rabo mai girma.

A waɗannan ayoyi bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci mugun halin munafukai maza da mata da mummunan sakamakonsu, sai kuma ya bayyana kyakkyawan halin muminai maza da mata, ya siffanta su da cewa, su masu ƙaunar junansu ne da son taimaka wa juna, suna umarni da kyakkyawan aiki suna kuma hana mummunan aiki, suna kuma tsayar da salla da haƙƙoƙinta kamar yadda aka umarce su, suna kuma bayar da zakka ga mutanen da suka cancanta a ba wa, sannan kuma suna yi wa Allah da Manzonsa biyayya. To waɗannan Allah ya yi alƙawalin zai yi musu rahama, lalle kuma Allah mabuwayi ne mai hikima.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Mumini dangantakarsa da ɗan'uwansa mumini kamar gini guda ne da sashensa yake ƙarfafar sashe." [Bukhari #2446, da Muslim #2585].

An karɓo daga Nu'umanu ɗan Bashir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Misalin muminai wajen ƙauna da jin ƙai da tausayin junansu kamar jiki guda ne, wanda idan wata gaɓa ba ta da lafiya sai sauran gaɓoɓin jiki su ɗauka su kamu da rashin barci da zazzaɓi." [Muslim #2587].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa muminai alƙawarin gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu; za su zauna a cikinsu har abada. Haka kuma zai ba su wasu kyawawan masaukai a cikin gidajen Aljanna, amma kuma yardar Allah a garesu ta fi musu ni'imar Aljannar. Wannan alƙawari kuwa shi ne babban rabo a gare su.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Akwai gidajen Aljanna iri biyu waɗanda ƙoransu da abin da yake cikinsu na azurfa ne, akwai kuma wasu biyu waɗanda ƙoransu da abin da yake cikinsu na zinare ne. Kuma babu abin da ya zama shamaki tsakanin 'yan Aljanna da ganin Ubangijinsu (a Aljanna) sai gwadon isa da ke kan fuskarsa, a cikin Aljanna ta dawwama". [Bukhari #7444, da Muslim #186].

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle mumini a Aljanna yana da wani tanti na rarakakken dutsen lu'u-lu'u guda ɗaya, tsawonsa mil sittin ne. Mumini yana da iyalinsa muminai a cikinsa, zai zagaya su amma sashensu ba zai ga ɗaya sashin ba." [Bukhari #3243, da Muslim #2838].

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah zai ce wa ‘yan Aljanna: “Ya ku ‘yan Aljanna.” Sai su ce: “Amsawarka ya Ubangijinmu, duk alheri yana hannunka.” Sai ya ce: “Kun kuwa gamsu?” Sai su ce: “Me zai sa ba za mu gamsu ba ya Ubangijinmu, alhalin ka ba mu abin da ba ka taɓa ba wani daga cikin halittarka ba?” Sai ya ce: “To ba na ba ku abin da ya fi wannan ba?” Sai ya ce: “Zan saukar muku da yardata ba zan yi fushi da ku ba har abada.” [Bukhari #7518, da Muslim #2829].

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan ‘yan Aljanna suka shiga Aljanna sai Allah mai girma da buwaya ya ce: “Kuna sha’awar wani abu in ƙara muku?” Sai su ce: “Ya Ubangijinmu, mene ne ya fi abin da ka ba mu?” Sai ya ce: “Yardata ce mafi girma.” [Ibn Hibban #7439, da Al-Hakim #276].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mayar da martani a kan masu yaɗa munanan aƙidu da bayyana hanyoyinsu na ɓata da na ɓarna a bisa hujja daga Allah da Manzonsa (ﷺ) wannan wani nau’i ne na jihadi.

2. A nan an haɗa munafukai tare da kafirai domin a faɗakar a kan cewa, dalilin da yake sawa a yaƙi kafirai tare da munafukai ya tabbata.

3. Duk wanda ya furta kalmar kafirci ko ya aikata aikin kafirci yana sane da gangan to ya kafirta ko da kuwa bai fito fili ya ce shi kafiri ne ba.

4. Tuba ga Allah shi ne tushen samun alherin duniya da lahira.

5. Kofar tuba a buɗe take ga duk wanda ya aikata laifi komai girmansa.

6. Wanda duk ya tsokano Allah da yaƙi, to babu mai iya kare shi daga azabarsa.

Suratut Tauba (73-74)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ جَٰهِدِ ٱلۡكُفَّارَ وَٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱغۡلُظۡ عَلَيۡهِمۡۚ وَمَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ٧٣ يَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ مَا قَالُواْ وَلَقَدۡ قَالُواْ كَلِمَةَ ٱلۡكُفۡرِ وَكَفَرُواْ بَعۡدَ إِسۡلَٰمِهِمۡ وَهَمُّواْ بِمَا لَمۡ يَنَالُواْۚ وَمَا نَقَمُوٓاْ إِلَّآ أَنۡ أَغۡنَىٰهُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ مِن فَضۡلِهِۦۚ فَإِن يَتُوبُواْ يَكُ خَيۡرٗا لَّهُمۡۖ وَإِن يَتَوَلَّوۡاْ يُعَذِّبۡهُمُ ٱللَّهُ عَذَابًا أَلِيمٗا فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِۚ وَمَا لَهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٍ ٧٤

73. Ya kai wannan Annabi, ka yaƙi kafirai da munafukai ka kuma tsananta musu. Jahannama ce kuma makomarsu. Makoma kuwa ta munana.

74. Suna rantsewa da Allah kan ba su faɗi (komai) ba, alhali kuwa tabbas sun faɗi kalmar kafirci, suka kuma kafirta bayan musuluntarsu, suka kuma yi ƙudirin aikata abin da ba su samu (dama) ba; ba kuwa abin da suke jin haushi sai kawai don Allah da Manzonsa sun wadata su daga falalarsa. To idan suka tuba zai fi musu alheri; idan kuwa suka juya baya to Allah zai azabtar da su azaba mai raɗaɗi a duniya da lahira; ba su da kuwa wani majiɓincin lamari ko wani mataimaki a bayan ƙasa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya yaƙi kafirai da munafukai, ya kuma matsa musu lamba sosai wajen wa’azi da tunkarar su da ƙarfafan hujjoji, kuma

makomarsu a lahira ita ce wutar Jahannama idan har sun bijire. Tir da wannan wuri da za su tsinci kansu a cikinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa munafukai suna rantsuwa da Allah a kan ƙaryar cewa su ba su furta komai ba da ya danganci kafirci, alhali kuwa sun furta kalmar kafirci, suka kuma kafirta bayan musuluntarsu, suka kuma ƙudurta mugun nufi na shirin kashe Manzon Allah (ﷺ) lokacin da yake komawa gida Madina daga yaƙin Tabuka, amma ba su ci nasara ba, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi kariya ya tsare shi daga sharrinsu. Babu kuma abin da yake baƙanta musu rai irin abin da ya kamata su yi godiya a kansa su yaba da shi, wato shi ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wadata su da falalarsa a dalilin aiko da Manzonsa (ﷺ) bayan a da suna matalauta. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, idan har suka tuba suka daina munafunci da kafirci, to wannan shi ya fi musu alheri; idan kuma suka bijire suka ƙi ba da gaskiya suka ƙi tuba, to Allah zai yi musu azaba mai raɗaɗi a duniya da lahira, kuma ba su da wani mai jiɓintar su da zai sama musu wani alheri, kuma babu mai taimakon su ya kare su daga azaba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saɓa alƙawari yana gadar da munafunci a zuciya. Don haka wajibi ne a kan Musulmi ya kula da alƙawarin da yake ɗauka, ya yi ƙoƙarin cika shi.

2. Duk munafuncin da ya kasance daga zuciya yake to wannan kafirci ne, wanda kuwa ya taƙaita a cikin ayyuka, to wannan saɓon Allah ne.

3. Duk wanda ya yi wa Allah alƙawarin yin wani kyakkyawan aiki, to wajibi ne a kansa ya aikata shi.

Suratut Tauba (75-78)

*وَمِنۡهُم مَّنۡ عَٰهَدَ ٱللَّهَ لَئِنۡ ءَاتَىٰنَا مِن فَضۡلِهِۦ لَنَصَّدَّقَنَّ وَلَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٧٥ فَلَمَّآ ءَاتَىٰهُم مِّن فَضۡلِهِۦ بَخِلُواْ بِهِۦ وَتَوَلَّواْ وَّهُم مُّعۡرِضُونَ ٧٦ فَأَعۡقَبَهُمۡ نِفَاقٗا فِي قُلُوبِهِمۡ إِلَىٰ يَوۡمِ يَلۡقَوۡنَهُۥ بِمَآ أَخۡلَفُواْ ٱللَّهَ مَا وَعَدُوهُ وَبِمَا كَانُواْ يَكۡذِبُونَ ٧٧ أَلَمۡ يَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ سِرَّهُمۡ وَنَجۡوَىٰهُمۡ وَأَنَّ ٱللَّهَ عَلَّٰمُ ٱلۡغُيُوبِ ٧٨

75. Daga cikinsu kuma akwai waɗanda suka yi wa Allah alƙawarin cewa: “Idan Ya arzuta mu daga falalarsa, to lalle tabbas za mu riƙa ba da sadaka, kuma lalle tabbas za mu zama cikin mutane salihai.”

76. To lokacin da Ya arzuta su ɗin sai suka yi rowa da ita (sadakar) suka kuma ba da baya suna masu bijirewa.

77. Sai Ya gadar musu da munafunci a cikin zukatansu har zuwa ranar da za su gamu da Shi, saboda saɓa wa alƙawarin da suka yi wa Allah da kuma ƙaryatawar da suka zamanto suna yi.

78. Yanzu ba su sani ba cewa, lalle Allah Ya san asirinsu da kuma ganawar da suke yi, lalle kuma Allah Shi ne cikakken Masanin gaibu?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da tona asirin munafukai, yana bayyana ƙarin wasu miyagun siffofinsu, da cewa, daga cikin munafukai akwai wanda ya yi wa Allah alƙawarin cewa, idan ya azurta shi daga falalarsa, to lalle zai yi sadaka ya fitar da haƙƙin Allah da ke cikin dukiyarsa da haƙƙin bayin Allah, to lokacin da Allah ya arzuta su daga falalarsa sai suka yi rowa suka juya wa Allah

baya suka ƙi cika alƙawarin da suka yi, sai Allah ya saka musu a kan haka, ya jefa musu munafunci a zukatansu wanda zai ci gaba da kasancewa tare da su har zuwa ranar mutuwarsu, su sadu da Allah suna munafukai, saboda saɓa alƙawarin da suka ɗauka tsakaninsu da Allah da kuma ƙaryar da suke sharawa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da cewa, yanzu su munafukai ba su san da cewa Allah yana sane da abin da suke ɓoyewa a zukatansu ba, da wanda suke asirta wa junansu, kuma Allah mai cikakken sanin gaibu ne?

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Alamomin munafuki uku ne: Idan ya yi magana sai ya yi ƙarya; idan kuma ya yi alƙawari sai ya saɓa; idan kuma aka amince masa sai ya ci amana." [Bukhari #33, da Muslim #59].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya yi bakin ƙoƙarinsa ya aikata alheri, to wajibi ne a ƙarfafa masa gwiwa a ƙara zaburar da shi. Munafukai sukan kushe wa irin waɗannan mutane domin su hana su ci gaba da aikata alheri.

2. Zunɗen mutum Musulmi da yi masa izgili yana daga cikin manyan laifuka a Musulunci.

3. Neman gafara ba ya amfani ga kafiri, hakanan aikinsa ba zai taɓa amfanar sa ba komai kyansa.

4. Nema wa muminai gafara zai amfane su.

5. Al'adar Allah ta gudana cewa, wanda ya yi nisa a cikin ɓata ba kasafai yake jin kira ba.

Suratut Tauba (79-80)

ٱلَّذِينَ يَلۡمِزُونَ ٱلۡمُطَّوِّعِينَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ فِي ٱلصَّدَقَٰتِ وَٱلَّذِينَ لَا يَجِدُونَ إِلَّا جُهۡدَهُمۡ فَيَسۡخَرُونَ مِنۡهُمۡ سَخِرَ ٱللَّهُ مِنۡهُمۡ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٧٩ ٱسۡتَغۡفِرۡ لَهُمۡ أَوۡ لَا تَسۡتَغۡفِرۡ لَهُمۡ إِن تَسۡتَغۡفِرۡ لَهُمۡ سَبۡعِينَ مَرَّةً فَلَن يَغۡفِرَ ٱللَّهُ لَهُمۡۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ كَفَرُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡفَٰسِقِينَ ٨٠

79. Waɗanda kuma suke aibata muminai masu yin sadaka (mai yawa) don neman lada da kuma waɗanda ba su da abin da za su bayar sai (kaɗan) gwargwadon wahalarsu, sannan su riƙa yi musu izgili, to Allah zai mayar musu da sakamakon izgilinsu, suna kuma da azaba mai raɗaɗi.

80. Ko ka nema musu gafara ko ba ka nema musu gafara ba (duk ɗaya ne). In da za ka nema musu gafara sau saba'in to Allah ba zai gafarta musu ba. Wannan kuwa saboda sun kafirce wa Allah da Manzonsa. Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane fasiƙai.

Waɗannan ayoyi suna ci gaba da bayanin siffofin munafukai ne. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana cewa, munafukai suna aibata muminai mawadata da suke sadaka mai yawa da dukiyoyinsu, suna ce musu wai ba don Allah suke yi ba; wai suna yi ne don riya; hakanan suna aibata muminai talakawa waɗanda suke sadaka da ɗan gwargwadon abin da Allah ya hore musu, sai su riƙa yi musu izgili da cewa, me Allah zai yi da 'yar wannan sadaka tasu; to su sani Allah zai saka musu a kan izgilinsu, kuma suna da wata azaba mai raɗaɗi a lahira.

An karɓo daga Abu Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da aka umarce mu da ba da sadaka a lokacin muna yin dako ne, sai Abu Aƙil ya kawo rabin sa'i (na dabino), wani mutum kuma ya kawo fiye da haka, sai munafukai suka ce: "Ai Allah ba ya buƙatar sadakar wannan (talakan), wannan kuwa riya ce kawai ya yi." Sai Allah ya saukar da wannan ayar. [Bukhari #4668, da Muslim #1018].

Ya zo a cikin hadisin Ka'abu ɗan Malik mai magana a kan yaƙin Tabuka cewa, Abu Khaisamata Al-Ansari shi ne ya kawo sadakar sa'i ɗaya na dabino, munafukai suka riƙa zunɗen sa. [Dubi, Muslim #1018].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Annabi cewa, ko ya nema wa munafukai gafarar Allah ko kada ya nema musu, Allah dai ba zai gafarta musu ba, ko da kuma ya nema musu gafara sau saba'in. Ba don wani abu ba sai don sun kafirce wa Allah da Manzonsa, Allah kuwa ba ya shiryar da mutane fasiƙai.
Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Da na san cewa idan na ƙara a kan saba'in za a gafarta musu, to lalle da na ƙara." [Dubi, Bukhari #1366].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Munafukai sune suke farin cikin zamansu a gida ba tare da sun fita yaƙi tare da Manzon Allah ba. Amma muminai masu uzuri da mutanen nan su uku da ba su fita tare da shi ba dukkansu ba sa farin cikin zamansu a gida da rashin fitarsu tare da Annabi (ﷺ).

2. Ya kamata ga wanda ba ya iya jure wa zafin rana a duniya ya yi tunanin guje wa aikata mummunan aiki wanda zai jawo masa shiga wutar Jahannama, domin babu mai iya jure zafinta.

3. Mumini da yake haƙuri da zafi da sanyi wajen ɗaukaka addinin Allah, yana kare kansa ne daga zafin wutar Jahannama da tsananin sanyinta, amma munafuki yana guje wa zafin duniya ne da sanyinta amma yana jefa kansa cikin na Jahannama.

Suratut Tauba (81-82)

فَرِحَ ٱلۡمُخَلَّفُونَ بِمَقۡعَدِهِمۡ خِلَٰفَ رَسُولِ ٱللَّهِ وَكَرِهُوٓاْ أَن يُجَٰهِدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَقَالُواْ لَا تَنفِرُواْ فِي ٱلۡحَرِّۗ قُلۡ نَارُ جَهَنَّمَ أَشَدُّ حَرّٗاۚ لَّوۡ كَانُواْ يَفۡقَهُونَ ٨١ فَلۡيَضۡحَكُواْ قَلِيلٗا وَلۡيَبۡكُواْ كَثِيرٗا جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٨٢

81. (Munafukai) waɗanda suka ƙi fita (yaƙi) sun yi farin ciki da zamansu (a gida) suna masu saɓa wa Manzon Allah, suka kuma ƙi su yi yaƙi da dukiyoyinsu da kawunansu saboda Allah, suka kuma ce (da junansu): "Kada ku fita yaƙi cikin zafin nan." Ka ce da su: "Wutar Jahannama ta fi tsananin zafi." Da sun zamanto suna ganewa.

82. Sai su yi dariya kaɗan su kuma yi kuka mai yawa a sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa.

A ci gaba da fallasar munafukai, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, munafukai waɗanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi watsi da su, bai datar da su a kan fita jihadi ba, sun riƙa nuna farin cikin zamansu a gida ba su fita yaƙi tare da Manzon Allah (ﷺ) zuwa Tabuka ba, don saɓa wa Manzon Allah, suka kuma ƙi su yi yaƙi ta hanyar ba da dukiyoyinsu da kawunansu don taimakon addinin Allah da ɗaukaka kalmarsa, suka ce wa junansu: Kada su kuskura su fita yaƙi tare da Musulmi zuwa birnin Tabuka

cikin wannan tsananin zafin rana." Allah ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, wutar Jahannama ai ta fi tsananin zafi da a ce suna ganewa suna kuma fahimtar abin da Allah yake faɗa musu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wutar da ɗan'adam yake kunnawa a duniya kaso ɗaya ne cikin saba'in na wutar Jahannama." Sahabbai suka ce: "Wallahi wutar duniya ma ta isa azaba." Sai ya ce: "To wutar Jahannama ta fi ta duniya da kaso sittin da tara, kowane kaso nata zafinsa kamar ta duniya ce." [Bukhari #6561, da Muslim #213].

Sannan Allah ya yi wa munafukai gatse da cewa, su yi dariya kaɗan a nan duniya, za su yi kuka mai yawa a ranar lahira yayin da aka jefa su wutar Jahannama. Wannan shi ne sakamakon kafircinsu da munafunci da saɓon Allah da suka dinga yi a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga Allah yana buƙatar samun wasu mutane waɗanda duk rintsi duk wahala ba za su girgiza ba kuma ba za su ja da baya ba. Don haka bai kamata a yi tafiya da waɗanda za su riƙa kawo cikas da yamutsi a cikin sahun masu gwagwarmaya ba ko waɗanda suke janye jikinsu lokacin wahala, amma sai su nemi dawowa lokacin daɗi. A'a, ana buƙatar masu dogewa ne a cikin kowane irin hali.

2. Babu taɓewar da ta kai ta mutumin da gaskiya ba ta buƙatar sa, take nesanta kanta da shi.

3. Duk wanda cutarwarsa da ha'incinsa suka bayyana ga abokin tafiyarsa, to wajibi ne ya watsar da shi ya yanke duk wata alaƙa tare da shi.

4. Wajibi ne mutum ya guji sakaci da wasa da abin da ya zama wajibi a kansa, domin duk sa'adda ya yi sakaci, to sai Allah ya dankwafar da shi ya hana shi aikata abin da zai jawo masa yardar Allah.

5. Duk wani mummunan aiki yana haifar da wani mummunan aiki irinsa, kamar yadda duk wani kyakkyawan aiki yake haifar da wani kyakkyawan aiki irinsa.

6. Masu neman duniya suna fifita ta a kan lahira za a yi musu azaba da ita, a jefa musu tsananin ƙaunar ta a zukatansu su yi ta wahala wajen tara ta, don haka sai su rayu zukatansu na cike da mayatar son ta da wahalar neman ta da tsaron ta.

7. Haramun ne a yi wa kafiri sallar janaza ko a yi masa addu'ar neman gafara da rahama bayan mutuwarsa.

8. Shar'anta sallatar mumini idan ya mutu da nema masa gafarar zunubansa da tsayawa a yi addu'a a kan ƙabarinsa.

9. Aya ta 84 tana nuna cewa, mamacin da aka binne yana amfana da addu'ar da masu tsayawa a kan ƙabarinsa suke yi masa. Don haka ne aka hana yi wa munafuki addu'a don wannan ya zama uƙuba gare shi.

10. Duk mai bayyana Musulunci a zahiri wajibi ne a gudanar masa hukunce-hukuncen shari'a na zahiri, kamar abin da ya shafi aure da gado da yi masa wanka bayan mutuwarsa da yi masa salla da binne shi. Amma wanda ya bayyana zindiƙancinsa da munafuncinsa a fili, to ba ya halatta ga duk wanda ya san haka daga gare shi ya sallace shi ko da kuwa yana bayyana Musulunci a zahiri.

Suratut Tauba (83-85)

فَإِن رَّجَعَكَ ٱللَّهُ إِلَىٰ طَآئِفَةٍ مِّنۡهُمۡ فَٱسۡتَ ٔ ذَنُوكَ لِلۡخُرُوجِ فَقُل لَّن تَخۡرُجُواْ مَعِيَ أَبَدٗا وَلَن تُقَٰتِلُواْ مَعِيَ عَدُوًّاۖ إِنَّكُمۡ رَضِيتُم بِٱلۡقُعُودِ أَوَّلَ مَرَّةٖ فَٱقۡعُدُواْ مَعَ ٱلۡخَٰلِفِينَ ٨٣ وَلَا تُصَلِّ عَلَىٰٓ أَحَدٖ مِّنۡهُم مَّاتَ أَبَدٗا وَلَا تَقُمۡ عَلَىٰ قَبۡرِهِۦٓۖ إِنَّهُمۡ كَفَرُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَمَاتُواْ وَهُمۡ فَٰسِقُونَ ٨٤ وَلَا تُعۡجِبۡكَ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَأَوۡلَٰدُهُمۡۚ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُعَذِّبَهُم بِهَا فِي ٱلدُّنۡيَا وَتَزۡهَقَ أَنفُسُهُمۡ وَهُمۡ كَٰفِرُونَ ٨٥

83. To idan Allah Ya dawo da kai zuwa ga wata jama’a daga cikinsu sai suka nemi izinin fita a wajenka, to sai ka ce (da su): “Ba za ku fita tare da ni ba har abada, kuma ba za ku yaƙi wani abokin gaba ba tare da ni ba har abada. Lalle kun yarda da zama tun farko, to sai ku zauna tare da masu zama.” (wato mata da yara).

84. Kada ka ƙara yi wa ɗaya daga cikinsu da ya mutu salla har abada, kada kuma ka tsaya a kan ƙabarinsa (don addu’a). Lalle su sun kafirce wa Allah da Manzonsa, suka kuma mutu suna fasiƙai.

85. Kada kuma dukiyoyinsu da ‘ya’yansu su ƙayatar da kai. Lalle kawai Allah Yana nufin azabtar da su ne da su (dukiyoyin da ‘ya’yan), rayukansu kuma su zazzago suna kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, idan Allah ya dawo da shi daga yaƙin Tabuka zuwa ga jama’a ta munafukai waɗanda suka yi zamansu a Madina suka ƙi bin sa ba tare da wani uzuri ba, sai kuma suka zo suna neman izinin fita wani yaƙin tare da shi, to ya faɗa musu cewa, ba za su ƙara fita yaƙi tare da shi ba har abada kuma ba za su ƙara yaƙar abokan gaba tare ba, saboda da farko sun yarda su zauna a gida su ƙi fita yaƙi a lokacin da aka nemi su fito tare da Annabi (ﷺ) zuwa yaƙin Tabuka. Don haka sai dai su yi ta zama a gida tare da yara da mata kamar yadda suka zaɓa a baya.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana Annabi (ﷺ) yi wa wani munafuki da ya mutu salla, ko ma ya tsaya a kan ƙabarinsa ya yi masa addu’a, saboda su munafukai sun kafirce wa Allah da Manzonsa sun kuma mutu suna fasiƙai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Lokacin da Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salulu ya mutu an kirawo Annabi (ﷺ) don ya sallace shi. To yayin da ya tsaya domin aikata hakan sai na zabura zuwa wajensa na ce: “Ya Manzon Allah (ﷺ), yanzu kai za ka sallaci ɗan Ubayyu alhalin a rana kaza da kaza ya faɗi kaza da kaza?” Na riƙa lissafa masa miyagun maganganunsa da ya taɓa faɗa ga Annabi (ﷺ). Sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi fushi, ya ce: “Kauce mini daga nan ya Umar.” Lokacin da na nace masa sai ya ce: “Haƙiƙa an ba ni zaɓi, ni kuma na zaɓa. Da a ce na san idan na ƙara a kan nema musu gafara sau saba’in za a gafarta musu to da na ƙara.” Annabi (ﷺ) ya sallace shi ya juya ya tafi. To ba da jimawa ba sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyin biyu na wannan Sura (aya ta 84-85).” Sai Umar ya ce: “Na yi mamakin irin ƙarfin hali da na nuna wa Manzon Allah (ﷺ) a ranar. Allah da Manzonsa su ne mafi sani.” [Bukhari #1366].
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa wa Manzonsa cewa, kada dukiyoyinsu da ‘ya’yansu su ƙayatar da shi, Allah yana nufin ya azabtar da su ne da waɗannan dukiyoyin da ‘ya’yan a nan duniya, sannan idan mutuwarsu ta zo rayukansu su fita daga jikkunansu suna kafirai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An fara yin umarni da imani kafin yin umarni da jihadi, domin idan babu imani jihadi ba zai yi amfani ba.

2. Dalilin ambaton ‘munafukai masu wadata’ saboda masu wadata su ne suke da ikon fita jihadi fiye da waɗanda ba su da wadata, sannan wanda ba shi da abin fita yaƙi shi da man an yi masa uzuri, don haka ba ya buƙatar neman izinin rashin fita.

3. Munafukai matsorata ne masu matacciyar zuciya, don haka suka zaɓi ƙaskanci da wulaƙanci.

4. Ba a wajabta wa mata yin jihadi ba ko da za su iya, don haka aka ambace su masu zaman gida ba a ce su fito ba.

5. Sahabban Manzon Allah (ﷺ) suna tare da shi koyaushe a cikin duk lamuransa, domin ya kirawo su sun kuma amsa kiransa, don haka suka yi yaƙi tare da shi da dukiyoyinsu da kawunansu.

6. Allah ya yi wa sahabban Annabi (ﷺ) alƙawarin Aljanna a ranar gobe ƙiyama.

7. Allah ya ba da shaida ga duk wanda ya je yaƙin Tabuka tare da Annabi (ﷺ) cewa suna tare da shi a Aljanna.
Suratut Tauba (86-89)

وَإِذَآ أُنزِلَتۡ سُورَةٌ أَنۡ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَجَٰهِدُواْ مَعَ رَسُولِهِ ٱسۡتَذَنَكَ أُوْلُواْ ٱلطَّوۡلِ مِنۡهُمۡ وَقَالُواْ ذَرۡنَا نَكُن مَّعَ ٱلۡقَٰعِدِينَ ٨٦ رَضُواْ بِأَن يَكُونُواْ
مَعَ ٱلۡخَوَالِفِ وَطُبِعَ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ فَهُمۡ لَا يَفۡقَهُونَ ٨٧ لَٰكِنِ ٱلرَّسُولُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ جَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلۡخَيۡرَٰتُۖ
وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ٨٨ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٨٩

86. Idan kuma aka saukar da wata sura mai cewa: “Ku yi imani da Allah kuma ku yi yaƙi tare da Manzonsa,” sai masu wadata daga cikinsu su nemi izininka su ce: “Kyale mu mu kasance tare da masu zama (a gida, wato mata da yara).”

87. Sun yarda da su kasance tare da mata masu zaman gida, an kuma doɗe zukatansu, saboda haka ba sa ganewa.

88. Sai dai shi Manzo da waɗanda suka yi imani tare da shi sun yi yaƙi da dukiyoyinsu da kuma kawunansu. Waɗannan kuwa suna da alherai; kuma waɗannan su ne marabauta.

89. Allah Ya tanadar musu da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu. Wannan shi ne rabo mai girma.

A waɗannan ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabi cewa, idan aka saukar da wata sura ta Alƙur’ani wadda a cikinta aka yi umarni da yin imani da Allah da fita jihadi tare da Manzonsa (ﷺ), to sai ka ga munafukai masu wadata sun zo suna neman izinin zama a gida, suna cewa a rabu da su su zauna a gida tare da mata da yara. Sun yarda su yi zamansu a gidajensu tare da mata ne, saboda Allah ya rufe musu zukatansu ruf don haka ba sa gane duk wani wa’azi da ake yi musu.
Sai dai waɗannan munafukai ya kamata su sani cewa, don sun yi zamansu sun ƙi fita yaƙi, wannan ba zai cutar da addinin Allah da komai ba, domin waɗanda suka fi su daraja a wurin Allah sun zabura wajen kare addinin Allah, su ne Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa, sun yi jihadi da dukiyoyinsu da kawunansu; to waɗannan Allah ya yi musu alƙawarin samun ni’imomi masu yawa a duniya da lahira, kuma su ne suka rabauta da ni’imar Aljanna. Allah ya yi musu tanadin gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudu ta ƙarƙashinsu, suna masu zama a cikinsu har abada; wannan kuwa shi ne babban rabo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ba shi da ikon aikata abin da ya wajaba a kansa, to wannan wajabcin ya faɗi daga kansa.

2. Wanda ya kyautata wa wani amma kyautatawar ta zo da wata tawaya ko gazawa to babu laifi ko tuhuma a kansa.

3. Duk ɗan'adam ajizi ne yana buƙatar gafarar Allah da rahama, domin ba komai da komai yake iya aikatawa ba.

4. Karfin imanin sahabbai da tsananin kwaɗayinsu ga alheri da ayyuka na ƙwarai, har ta kai sukan yi kuka saboda sun rasa damar aikata wani aikin alheri.

5. Samun dukiyar da za ta taimaka wa mutum ya aikata alheri ya fi rashinta.

Suratut Tauba (90-93)

وَجَآءَ ٱلۡمُعَذِّرُونَ مِنَ ٱلۡأَعۡرَابِ لِيُؤۡذَنَ لَهُمۡ وَقَعَدَ ٱلَّذِينَ كَذَبُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥۚ سَيُصِيبُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٩٠ لَّيۡسَ عَلَى ٱلضُّعَفَآءِ وَلَا عَلَى ٱلۡمَرۡضَىٰ وَلَا عَلَى ٱلَّذِينَ لَا يَجِدُونَ مَا يُنفِقُونَ حَرَجٌ إِذَا نَصَحُواْ لِلَّهِ وَرَسُولِهِۦۚ مَا عَلَى ٱلۡمُحۡسِنِينَ مِن سَبِيلٖۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٩١ وَلَا عَلَى ٱلَّذِينَ إِذَا مَآ أَتَوۡكَ لِتَحۡمِلَهُمۡ قُلۡتَ لَآ أَجِدُ مَآ أَحۡمِلُكُمۡ عَلَيۡهِ تَوَلَّواْ وَّأَعۡيُنُهُمۡ تَفِيضُ مِنَ ٱلدَّمۡعِ حَزَنًا أَلَّا يَجِدُواْ مَا يُنفِقُونَ ٩٢ ۞إِنَّمَا ٱلسَّبِيلُ عَلَى ٱلَّذِينَ يَسۡتَـٔۡذِنُونَكَ وَهُمۡ أَغۡنِيَآءُۚ رَضُواْ بِأَن يَكُونُواْ مَعَ ٱلۡخَوَالِفِ وَطَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ فَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٩٣

90. Masu kawo uzurin ƙarya daga mutanen ƙauye kuma suka zo don a yi musu izini, sai kuma waɗanda suka yi wa Allah da Manzonsa ƙarya suka yi zamansu (ba tare da kawo hanzari ba). To azaba mai raɗaɗi za ta samu waɗanda suka kafirta daga cikinsu.

91. Babu wani laifi a kan raunana ko marasa lafiya ko kuma waɗanda ba su samu abin da za su ciyar ba (don talauci), matuƙar dai sun tsarkake zuciyarsu ga Allah da Manzonsa. Babu wata hanya (ta ɗora laifi) ga masu kyautatawa. Allah kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

92. Haka kuma babu (laifi) a kan waɗanda idan sun zo maka don ka ba su abin hawa sai ka ce: "Ba ni da abin hawan da zan ba ku," sai suka juya idanuwansu suna kwararar da hawaye don baƙin cikin ba su sami abin da za su ciyar ba.

93. Zargi kawai yana kan waɗanda suke neman izininka alhali kuwa suna mawadata. Sun yarda da su kasance tare da masu zaman gida (mata da yara). Allah kuma Ya doƙe zukatansu, saboda haka ba sa sanin (gaskiya).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa Larabawan ƙauye sun yi ta zuwa wurin Manzon Allah (ﷺ) suna kawo masa uzurin ƙarya da ya ba su izinin zama a gida kada su fita yaƙi tare da shi, su kuma munafukai waɗanda suka yi wa Allah da Manzonsa ƙaryar da'awar imani suka yi zamansu ba su ma zo da wani uzuri ba. Allah ya ba da labarin cewa wata azaba mai raɗaɗi za ta sami waɗanda suka kafirta daga cikin Larabawan ƙauyen nan masu kawo uzurin ƙarya.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zayyana uzururrukan da za su hana fita jihadi, inda ya ce, babu laifi a kan raunanan mutane da marasa lafiya da waɗanda ba su da guzurin fita don sun zauna ba su fita tare da Annabi (ﷺ) ba, matuƙar dai sun kansance sun tsarkake imaninsu da ayyukansu da niyyoyinsu ga Allah da taimakon addininsa da Annabinsa (ﷺ). Don haka babu wata hanya ta ɗora laifi a kan masu kyautatawa. Allah kuma mai yawan gafara ne mai jin ƙai, yana kuma yafe wa wanda ya yi laifi ya tuba, yana jin ƙan su ba ya yi musu azaba.
Sannan aka bayyana hukuncin masu kawo uzurin ƙarya domin kada su fita jihadi tare da Manzon Allah (ﷺ), aka tabbatar da cewa, su ne za a azabtar domin suna ƙin fita ne duk da cewa su mawadata ne suna da abin hawa da makaman yaƙi da guzuri, amma sun yarda su zauna gida tare da mata. Allah kuma ya rufe zukatansu ruf wani alheri ba ya shigar su, saboda haka ba sa sanin gaskiya su yi aiki da ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana da kyau mutum ya guji aikata abin da zai dawo daga baya yana ba da hanzari.

2. Aiki shi ne ma’aunin gane ƙarya da gaskiya ba maganganun fatar baki ba kawai.

3. Duk abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai yarda da shi ba to bai kamata muminai su yarda da shi ba.

4. Wanda aka san shi maƙaryaci ne, to bai kamata a yi saurin karɓar uzurinsa ba.

5. Ana yi wa munafukai hukunci da abin da ya bayyana ne na ayyukansu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne zai jiɓinci hukunci a kan abin da suka ɓoye a zukatansu.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya son muminai su yarda da mutane fasiƙai, domin shi ba zai yarda da su ba.

Suratut Tauba (94-96)

يَعۡتَذِرُونَ إِلَيۡكُمۡ إِذَا رَجَعۡتُمۡ إِلَيۡهِمۡۚ قُل لَّا تَعۡتَذِرُواْ لَن نُّؤۡمِنَ لَكُمۡ قَدۡ نَبَّأَنَا ٱللَّهُ مِنۡ أَخۡبَارِكُمۡۚ وَسَيَرَى ٱللَّهُ عَمَلَكُمۡ وَرَسُولُهُۥ ثُمَّ تُرَدُّونَ إِلَىٰ عَٰلِمِ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ٩٤ سَيَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ لَكُمۡ إِذَا ٱنقَلَبۡتُمۡ إِلَيۡهِمۡ لِتُعۡرِضُواْ عَنۡهُمۡۖ فَأَعۡرِضُواْ عَنۡهُمۡۖ إِنَّهُمۡ رِجۡسٞۖ وَمَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ٩٥ يَحۡلِفُونَ لَكُمۡ لِتَرۡضَوۡاْ عَنۡهُمۡۖ فَإِن تَرۡضَوۡاْ عَنۡهُمۡ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يَرۡضَىٰ عَنِ ٱلۡقَوۡمِ ٱلۡفَٰسِقِينَ٩٦

94. Za su kawo muku uzurinsu idan kuka dawo musu. Ka ce: “Kada ku kawo wani uziri, mu ba za mu gaskata ku ba har abada, haƙiƙa Allah ya faɗa mana labarinku. Allah kuwa zai ga ayyukanku Shi da Manzonsa, sannan a komar da ku zuwa ga Masanin abin da yake ɓoye da na sarari, sai Ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa.”

95. Za su rantse muku da Allah idan kuka dawo wurinsu don ku ƙyale su. To ku ƙyale su ɗin. Lalle su najasa ne; makomarsu kuma wutar Jahannama ce sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa.

96. Suna rantse muku don ku yarda da su; to idan ma kun yarda da su ɗin, lalle (Shi) Allah ba zai yarda da mutane fasiƙai ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa muminai cewa, munafukan da suka ƙi fita yaƙi ba tare da suna da wani uzuri ba, idan muminai sun dawo daga jihadinsu za su zo suna kawo musu uzururruka na ƙarya, sai Allah ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa musu cewa, kada ma su ce za su kawo wani uzuri, Annabi da sauran muminai ba za su yarda da su ba, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da su asirinsu, sun gane ƙarairayinsu, kuma Allah zai ga aikinsu, hakanan Manzonsa zai gani inda gaskiyarsu da ƙaryarsu za su bayyana. Sannan bayan mutuwarsu za a mayar da su ga Masanin ɓoye da sarari shi ne Allah, kuma zai ba su labarin duk abin da suka riƙa aikatawa a duniya kuma ya yi musu sakayya a kai.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan munafukai za su yi wa muminai rantsuwa da Allah yayin da suka dawo daga Tabuka, su nuna musu cewa su ba sun ƙi fita ne da gangan ba, abin ne ya fi ƙarfinsu, domin muminai su ƙyale su, ba za su zarge su a kan ƙin fita da gangan ba. Allah ya umarci muminai da cewa su ƙyale su ɗin, don wannan ya zamo wulaƙanci gare su, domin su najasa ne, makomarsu kuma a ranar lahira ita ce wutar Jahannama saboda abin da suka riƙa aikatawa na kafirci da munafunci da saɓon Allah da Manzonsa.
Ya kuma ƙara da cewa, munafukan za su yi ta yi musu rantsuwa don su yarda da su, to amma ko da sun yarda da su, yardar ba za ta amfane su da komai ba, don haka su ma muminai kada su yarda da su domin Allah ba zai taɓa yarda da mutane fasiƙai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar ilimi. Duk mutumin da ya rasa ilimi dab yake da faɗawa cikin wani sharri ko ɓata fiye da wanda Allah ya ba shi ilimi.

2. Ilimi mai amfani shi ne sanin dokokin Allah waɗanda ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) kamar ilimin Tauhidi da na furu'a da abin da zai haifar wa da bawa tsoron Allah da kauce wa saɓa masa.

3. Kafirci da munafunci su ma suna ƙaruwa suna kuma raguwa gwargwadon yadda halayyar kowane mutum take.

4. Mutanen ƙauye sau tari suna da kaushin hali da ƙeƙashewar zuciya fiye da mazauna birni, shi ya sa Allah ba ya aiko da manzanni daga mutanen ƙauyuka.

5. Muhimmancin yaɗa ilimin addini a ƙauyuka, domin buƙatarsu gare shi ta fi tsanani a kan ta mazauna birane.

Suratut Tauba (97-98)

ٱلْأَعْرَابُ أَشَدُّ كُفْرًا وَنِفَاقًا وَأَجْدَرُ أَلَّا يَعْلَمُوا۟ حُدُودَ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٩٧﴾ وَمِنَ ٱلْأَعْرَابِ مَن يَتَّخِذُ مَا يُنفِقُ مَغْرَمًا وَيَتَرَبَّصُ بِكُمُ ٱلدَّوَآئِرَ ۚ عَلَيْهِمْ دَآئِرَةُ ٱلسَّوْءِ ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٩٨﴾

97. Mutanen ƙauye sun fi tsananin kafirci da munafunci, kuma su suka fi dacewa da rashin sanin dokokin da Allah Ya saukar wa Manzonsa. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima.

98. Daga mutanen ƙauye kuma akwai waɗanda suke ɗaukar abin da suke ciyarwa tara ne, suke kuma jiran faruwar masifu gare ku. To mummunar masiba ta tabbata a kansu. Allah kuma Mai ji ne, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin cewa, ƙauyawa sun fi tsananin kafirci da munafunci fiye da ‘yan birni, sannan su suka fi dacewa da rashin sanin halal da haram da sauran dokokin da Allah ya saukar wa Annabi (ﷺ). Allah kuwa masani ne mai hikima cikin dukkan lamarinsa. Daga cikin ƙauyawa akwai wanda yake ɗaukar dukiyar da yake bayarwa wajen aikin alheri kamar tara ce Annabi (ﷺ) yake karɓa a hannunsa, don haka yana ganin hasara kawai yake yi; yana dai bayarwa ne kawai ba don yana so ko yana fatan samun wani lada daga Allah ba. Hasali ma yana sauraron faruwar wani mummunan abu ne ga Musulmi, kamar a ce maƙiyansu sun yi nasara a kansu, har ma duk al’amuransu su lalace. To amma sai Allah ya mayar musu da aniyarsu, mummunan abu ya tabbata a kansu wanda zai dugunzuma rayuwarsu gaba ɗaya. Allah kuma mai ji ne ga dukkan maganganunsu, kuma masanin abin da yake cikin zukatansu ne, don haka zai yi musu sakayya da abin da suka cancanta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk alhairin da mutum zai aikata, to ya aikata shi don neman kusanci ga Allah da fatan samun sakamakonsa ranar lahira.

2. Bayanin cewa mutanen ƙauye su ma kamar na birane suke, a cikinsu akwai na kirki akwai na banza, ba duk suka taru suka zama ɗaya ba.

3. Ciyar da dukiya don Allah yana ƙara wa mai shi kusanci ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Falalar sahabban Annabi (ﷺ), musamman Musulman farko daga cikinsu waɗanda suka ba da gaskiya da Annabi (ﷺ) sannan suka yi hijira tare da shi zuwa Madina, da muminan farko na mutanen Madina waɗanda suka rungumi Annabi (ﷺ) da sahabbansa lokacin da suka yi hijira zuwa gare su, waɗannan sun fi girman falala a kan waɗanda suka zo bayansu.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, haƙiƙa ya yarda da sahabban farko da suka ba da gaskiya cikin mutanen Makka da na Madina. Don haka aka yi tir da wanda ba ya son su ko yake zagin su ko yake aibata su, musamman mafi falalarsu kuma shugabansu Sayyidina Abubakar As-Siddiƙ. Mabiya addinin Shi’a su ne suke nuna ƙiyayya gare su, suna zagin su, suna aibata su. Wannan ya nuna gurɓacewar zukatansu da lalacewar tunaninsu. Saɓanin masu bin sunnar Manzon Allah (ﷺ) su kam suna son su baki ɗayansu, suna kuma nema musu gafara da rahama da yardar Allah, suna kuma nuna ƙauna da soyayya ga duk mai son su, suna nuna ƙiyayya da gaba ga duk mai ƙin su.

6. Wajibi ne a yi wa sahabbai biyayya, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabe su har da waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yardarsa ga sahabbai magabata daga masu hijira da mutanen Madina kai-tsaye ba tare da wani sharaɗi ba; ya kuma bayyana yardarsa ga waɗanda suka biyo bayansu amma kuma da sharaɗin ‘kyautatawa’.

8. Tabbacin cewa sahabbai magabata za su mutu da imani, wanda da shi ne za su cancanci samun yardar Allah.

9. Duk wanda Allah ya ce ya yarda da shi, to wannan mutum ɗan Aljanna ne babu wani kokwanto.

10. Cika baki na nuna biyayya ga sahabbai ba zai amfani mutum ba har sai ya kyautata aikinsa, ta hanyar aikata wajibai da kauce wa haramun.

Suratut Tauba (99-100)

وَمِنَ ٱلۡأَعۡرَابِ مَن يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَيَتَّخِذُ مَا يُنفِقُ قُرُبَٰتٍ عِندَ ٱللَّهِ وَصَلَوَٰتِ ٱلرَّسُولِۚ أَلَآ إِنَّهَا قُرۡبَةٞ لَّهُمۡۚ سَيُدۡخِلُهُمُ ٱللَّهُ فِي رَحۡمَتِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٩٩ وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلۡأَوَّلُونَ مِنَ ٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُم بِإِحۡسَٰنٖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُ وَأَعَدَّ لَهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي تَحۡتَهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١٠٠

99. Daga mutanen ƙauye ɗin kuma akwai waɗanda suke yin imani da Allah da ranar lahira, suke kuma ɗaukar abin da suke ciyarwa (hanyoyi ne) na samun kusanci ga Allah da kuma addu'o'in Manzo. Lalle wannan ibada ce gare su. Allah zai shigar da su cikin rahamarsa. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

100. Magabata kuwa na farko daga cikin masu hijira da Ansaru da kuma waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa, (duka) Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi, Ya kuma tanadar musu gidajen Aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada. Wannan shi ne rabo mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, mutanen ƙauye ba duka suka taru suka zama ɗaya ba; daga cikinsu akwai ƙauyawa masu imani da Allah da Manzonsa (ﷺ) da ranar alƙiyama, sannan suke yarda cewa abin da suke ciyarwa na dukiyarsu wasu hanyoyi ne masu kusanta su da Allah, suke kuma neman addu'o'in Manzon Allah (ﷺ) da wannan sadakar tasu, wato lokacin da zai karɓi zakkarsu ko sadakarsu. Tabbas wannan sadakar tasu da kuma addu'o'in Annabi (ﷺ) ibada ce babba mai kusantar da su ga Allah, don haka Ubangijinsu zai shigar da su cikin rahamarsa. Lalle Allah mai gafara ne mai jin ƙai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana matsayin sahabban Annabi (ﷺ) waɗanda su ne magabata na farko da suka yi imani kuma suka yi hijira daga Makka zuwa Madina, da kuma su muminai mutanen Madina waɗanda suka taimaka wa Annabi (ﷺ) da sahabbansa lokacin da suka je Madina suna baƙi ba su san kowa ba, da kuma sauran muminai waɗanda suka biyo bayansu, suka kuma bi hanyarsu madaidaiciya ta imani da kyakkyawan aiki, to duka waɗannan Allah ya yarda da su, su ma sun yarda da Allah, ya kuma yi musu tanadin gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su shige su, kuma dawwama a cikinsu har abada; wannan kuwa shi ne babban rabo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu munafuki ko ɗaya a cikin mutanen Makka. An same su ne kawai a cikin ƙabilun Madina, yayin da Musulunci ya shigo garin, ƙabilun Ausu da Khazraju suka musulunta. To bayan Musulunci ya yi ƙarfi Musulmi suna iya yaƙi su kare kansu sai aka samu waɗanda suka shiga Musulunci don tsoro ko ɓoye kansu, don haka sai suka zama munafukai.

2. Wanda duk bai yi iƙirari da laifinsa ba daga cikin waɗannan mutane to shi munafuki ne.

3. Tunda har Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce Manzonsa bai san su ba, shi ne ya san su, to babu wanda ya isa ya yi da'awar ya san abin da ke cikin zukatan mutane kuma ya zamanto mai gaskiya.

4. Duk wanda ya cakuɗa ayyukansa masu kyau da wasu munana, tare da yin nadama da iƙirarin laifinsa, to wannan yana ƙarƙashin tsoro da fata, to amma an fi yi masa zaton kuɓuta a wurin Allah. Amma wanda ya gauraya kyawawan ayyukansa da munana, sannan ya ƙi yin iƙirari da nadama a kan laifinsa, to wannan ana jiye masa tsoron haɗuwa da azabar Allah.

5. Abu Usman An-Nahdi yana cewa: A Alƙur'ani gaba ɗaya a wurina babu wata aya da ta fi jefa kyakkyawan fata ga wannan al'umma kamar wannan ayar ta 102. [Dubi, Suyuɗi, *Ad-Durrul Manthu*r, Juzu'i na 4, aya ta 278].

6. Wannan ayar ta shafi dukkan mutanen da suka yi wa Allah laifi ne, sai kuma zukatansu suka cika da nadama da tsoron Allah.

7. Duk lokacin da mai laifi ya yarda da laifinsa ya kuma yi nadama, to wannan ya yi tuban da Allah zai karɓa.

8. Abin lura a aya ta 101 shi ne, munafukai iri biyu ne; kaso na farko an gane su ta hanyar maganganunsu da ayyukansu da suka riƙa nunawa a fili; kaso na biyu kuwa sun ƙware a kan munafunci, ba wanda yake iya gane su ko ya ga wata alamar munafunci a tare da su. Haka kuwa ake samun duk kason biyu a kowane zamani.

9. Tabbatar da azabar ƙabari, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci azaba uku ne a aya ta 101: Ta farkon ita ce azabar duniya, ta biyun kuwa ita ce ta ƙabarin, sai ta lahira ita ce ta ukun.

10. Duk wanda ya kasance mumini sannan ya yi aikinsa don Allah, to Allah ba zai zalunce shi ba; zai saka masa ne a kan haka. Amma abin da zai aikata na haramun, aiki ɗan kaɗan, sai ya cancanci a yi masa uƙuba a kansa, amma ana sa ran ya tuba ga Allah. Idan kuwa ya mutu bai tuba ba, to wannan al'amarinsa na ga Allah, shi ne ya fi sanin gwargwadon yawan kyawawan ayyukansa da munana, ba za a yi masa shaida da Aljanna ko wuta ba, saɓanin aƙidar Khawarijawa da Mu'utazilawa, masu cewa duk wanda ya aikata laifi babba, to duka kyawawan ayyukansa sun rushe. Amma a wurin Ahlussunna ba sa cewa ayyukansa sun rushe; a wurinsu masu manyan laifuka tare da kyawawan ayyuka al'amarinsu yana wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratut Tauba (101-102)

وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلۡأَوَّلُونَ مِنَ ٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُم بِإِحۡسَٰنٖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُ وَأَعَدَّ لَهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي تَحۡتَهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١٠٠ وَمِمَّنۡ حَوۡلَكُم مِّنَ ٱلۡأَعۡرَابِ مُنَٰفِقُونَۖ وَمِنۡ أَهۡلِ ٱلۡمَدِينَةِ مَرَدُواْ عَلَى ٱلنِّفَاقِ لَا تَعۡلَمُهُمۡۖ نَحۡنُ نَعۡلَمُهُمۡۚ سَنُعَذِّبُهُم مَّرَّتَيۡنِ ثُمَّ يُرَدُّونَ إِلَىٰ عَذَابٍ عَظِيمٖ ١٠١ وَءَاخَرُونَ ٱعۡتَرَفُواْ بِذُنُوبِهِمۡ خَلَطُواْ عَمَلٗا صَٰلِحٗا وَءَاخَرَ سَيِّئًا عَسَى ٱللَّهُ أَن يَتُوبَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٠٢

101. Kuma daga mutanen ƙauye waɗanda suke kewaye da ku akwai munafukai, haka kuma daga mutan Madina; sun ƙware a kan munafunci, kai ba ka san su ba; Mu ne Muka san su. Za Mu azabtar da su sau biyu, sannan a komar da su zuwa ga azaba mai girma.102. Wasu kuwa sun yi iƙirari da laifinsu, sun

gauraya kyakkyawan aiki da wani mummuna, to tabbas Allah zai karɓi tubansu. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, daga cikin mazauna ƙauyukan da suke zagaye da Madina akwai munafukai, hakanan a cikin mazauna Madina ma akwai su, sun ƙware sosai a kan munafunci har ya zamar musu jiki, kuma sun doge a kansa sun ƙi su tuba. Amma Allah ya ce shi ya san su Annabi (ﷺ) ne bai san su ba, Allah kuma ya yi alƙawarin sai ya yi musu azaba sau biyu, azabar duniya da ta ƙabari, sannan ranar alƙiyama ya mayar da su zuwa azaba mai girma.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, akwai mutanen da suka yi iƙirari da laifinsu, watau sun haɗa kyakkyawan aiki da mummuna, su kam wataƙila Allah ya karɓi tubansu. Waɗannan su ne mutanen kirki waɗanda su ba munafukai ne ba, suna da ayyukan ƙwarai amma sai ba su fita yaƙin Tabuka tare da Manzon Allah (ﷺ) ba, daga baya suka tuba Allah kuma ya karɓi tubansu. Haƙiƙa Allah mai gafara ne ga duk wanda ya tuba, mai jin ƙai ne gare su ba zai yi musu azaba ba.

An karɓo daga Samuratu ɗan Jundab (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce mana: “A daren jiya wasu mala’iku biyu sun zo mini, suka tashe ni daga barci, suka tafi da ni har zuwa wani birni wanda aka gina shi da tubalan zinare da na azurfa, sai wasu mutane suka tarye mu, rabin halittarsu na da kyau matuƙa, rabinta kuwa yana da matuƙar muni, sai mala’ikun nan biyu suka ce musu: ‘Ku je ku faɗa cikin waccan ƙoramar.’ Sai suka je suka tsunduma cikinta, suka dawo duk wannan munin ya rabu da su, sun yi matuƙar kyan kamanni. Sai mala’ikun suka ce mini: ‘Wannan ita ce Aljannar dawwama, wancan kuma gidanka ne, waɗannan mutanen kuwa waɗanda rabinsu mai kyau ɗaya rabin nasu mummuna su ne waɗanda suka gauraya aiki mai kyau da mummunan aiki, sai kuma Allah ya yafe musu.’ [Bukhari #4674].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bawa ba zai taɓa tsarkaka ba har sai ya fitar da zakkar dukiyarsa.

2. Wajabcin karɓar zakka daga dukiyoyin Musulmi: Kadarorin kasuwanci ko tsabar kuɗi ko kayan amfanin gona ko kuma dabbobin kiwo.

3. Bayanin cewa shugaba a wuyansa ne alhakin karɓo zakka ya rataya.

4. Mustahabbi ne idan shugaba ya karɓi zakkar mutum, to ya yi masa addu’a mai kyau, kuma ya yi ta a bayyane yadda mai zakkar zai ji da kunnensa ya ƙara samun nutsuwa a ransa.

5. Kyawawan ayyuka suna tsarkake zukata su wanke su daga zunubansu.

6. Umarnin Annabi ya karɓi zakka, yana nuna cewa ana karɓar ta ko da da ƙarfi ne daga hannun wanda ya hana ta da lalama.

7. Mumini yana amfana da addu’ar ɗan’uwansa mumini.

8. Yana da kyau a zaburar da wanda ya ciyar da dukiyarsa ko ya yi wani kyakkyawan aiki ta hanyar yi masa addu’a ta ƙwarai da yaba masa ƙoƙarinsa.

Suratut Tauba (103-104)

خُذۡ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡ صَدَقَةٗ تُطَهِّرُهُمۡ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيۡهِمۡۖ إِنَّ صَلَوٰتَكَ سَكَنٞ لَّهُمۡۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ١٠٣ أَلَمۡ يَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ هُوَ يَقۡبَلُ ٱلتَّوۡبَةَ عَنۡ عِبَادِهِۦ وَيَأۡخُذُ ٱلصَّدَقَٰتِ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٤

103. Ka karɓi sadaka daga dukiyoyinsu da za ka tsarkake su kuma ka gyara musu halaye da ita, ka kuma yi musu addu'a. Lalle addu'arka nutsuwa ce a gare su. Allah kuwa Mai ji ne, Masani.

104. Shin yanzu ba su sani ba ne cewa Allah shi Yake karɓar tuba daga bayinsa Yake kuma karɓar sadakoki, kuma lalle Shi ne Mai yawan karɓar tuba, Mai jin ƙai?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya karɓi zakka daga dukiyoyin Musulmi mawadata, don ya tsarkake su daga dauɗar zunubansu da wannan zakkar, kamar yadda ya umarce shi da yi musu addu'a lokacin da yake karɓar zakkarsu, domin addu'arsa nutsuwa ce a gare su da hutu ga zukatansu. Allah mai ji ne masani.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Sadaka kuwa tana gusar da laifi kamar yadda ruwa yake kashe wuta." [Ahmad #15284, da Abu Ya'la #1999, da Ibn Hibban #1723].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abu Aufa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance idan mutane suka zo masa da sadakarsu sai ya karɓa ya ce: "Ya Allah, ka yi musu salati." Sai baban Abu Aufa ya zo masa da sadakarsa sai ya ce: "Allah ka yi salati ga iyalan Abu Aufa." [Bukhari #1497, da Muslim #1078].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da cewa, shin yanzu ba su sani ba ne cewa Allah ne kaɗai yake karɓar tuban waɗanda suka tuba, kuma yake karɓar sadakar bayinsa, kuma shi ne mai yawan karɓar tuba mai yawan rahama?

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda.) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Babu wanda zai bayar da sadaka daga dukiyarsa ta halal mai tsarki-Allah ba ya karɓa sai mai tsarki-face Allah mai rahama ya karɓe ta da hannunsa na dama, ko da kuwa ƙwayar dabino ne, haka zai karɓe shi ya yi ta haɓaka a hannun Allah mai rahama har sai ya fi tsauni girma, kamar yadda ɗayanku yake rainon dukushin dokinsa ko ɗan marakinsa." [Bukhari #1410, da Muslim #1014].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matakin bayyana gaskiyar tubar bawa shi ne aikinsa na sarari. Nadama da tuba ba su ne ƙarshe ba, dole ne sai aiki na ƙwarai ya biyo bayansu.

2. Faɗarsa: "Ka kuma ce musu: 'Ku yi aiki, Allah ne zai ga aikin naku.'" babbar kwaɗaitarwa ce ga masu ɗa'a, kuma tsoratarwa ce mai girma ga masu laifuka. Kamar yana ce musu ne, ku yi aiki nan gaba domin ayyukanku suna da hukunci a duniya, suna da shi a lahira; hukuncinsu na duniya Allah da Manzonsa da muminai za su ga ayyukanku, idan ɗa'a ce kuka yi wa Allah ku samu kyakkyawan yabo da babban sakamako a duniya da lahira. Idan kuwa saɓon Allah kuke yi, sai ku samu mummunan shaida a duniya, a lahira kuma ku haɗu da azaba mai tsanani.

3. Tsoratarwa a kan sakaci wajen aikin alheri ko kuma aikata saɓon Allah, domin jin cewa Allah yana ganin abin da mutum yake aikatawa zai sa shi (mutum) ƙoƙarin neman yardarsa da kauce wa fushinsa.

Suratut Tauba (105-106)

وَقُلِ ٱعۡمَلُواْ فَسَيَرَى ٱللَّهُ عَمَلَكُمۡ وَرَسُولُهُۥ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۖ وَسَتُرَدُّونَ إِلَىٰ عَٰلِمِ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ١٠٥ وَءَاخَرُونَ مُرۡجَوۡنَ لِأَمۡرِ ٱللَّهِ إِمَّا يُعَذِّبُهُمۡ وَإِمَّا يَتُوبُ عَلَيۡهِمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ١٠٦

105. Ka kuma ce: “Ku yi aiki, Allah ne zai ga aikinku shi da Manzonsa da kuma muminai, kuma za a mayar da ku zuwa ga Masanin abin da yake ɓoye da na sarari, sannan Ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa.

106. Wasu kuwa an jinkirta lamarinsu ne ga hukuncin Allah, ko dai ya azabtar da su ko kuma Ya karɓi tubarsu. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) cewa, ya faɗa wa waɗannan da suka ƙi fita yaƙi kuma suka zo suka ba da hanzari sannan suka tuba cewa, su yi aiki Allah ne zai ga aikinsu na zahiri da na baɗini, ya kuma yi musu sakayya a kai, hakanan Manzonsa (ﷺ) da muminai su ma za su ga abin da Allah ya nuna musu na ayyukansu don su yi musu shaida a kai mai kyau ko marar kyau.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wasu mutane sun wuce ɗauke da wata gawa sai sahabbai suka faɗi alherin wannan mamacin, sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Ta wajaba.” Sai wasu kuma suka sake wucewa da wata gawar, sai sahabbai suka yi mata mummunar shaida, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ta wajaba.” Sai Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Mece ce ta wajaba?” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Kun faɗi alheri a kan na farko sai Aljanna ta wajaba gare shi. Wannan kuwa kun bayar da mummunar shaida a kansa sai wuta ta wajaba a kansa; ku ne masu bayar da shaida a bayan ƙasa.” [Bukhari #1367].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, za a mayar da su zuwa ga Allah ranar alƙiyama, wanda shi ne masanin abin da yake ɓoye da na sarari, zai kuma ba su labarin abin da suka kasance suna aikatawa.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, cikin waɗanda suka ƙi fita yaƙin Tabuka akwai wasu mutane da aka jinkirtar da lamarinsu aka mayar da hukuncinsu ga Allah, shi ne wanda zai yi musu hukunci ranar alƙiyama da abin da ya ga dama; ko dai ya yi musu azaba ko kuma ya karɓi tubarsu. Allah kuma masani ne mai hikima; ya san kowane ɓangare da halayyarsa da abin da yake cikin zukatansu, ko sun cancanci uƙuba ko kuma sun cancanci afuwa, yana sanya hukuncinsa a inda ya dace, yana kuma da hikima cikin duk maganganunsa da ayyukansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saɓon Allah yana yin tasiri a wuri kamar yadda ɗabi’a take yi. Saɓon da munafukai suke yi dangane da masallacin nan na cutarwa ya yi tasirin da har Allah ya hana Manzonsa (ﷺ) yin salla a cikinsa. Hakanan ɗa’a ga Allah ta yi tasiri a masallacin Kuba har Allah ya nuna cancantar yin salla a cikinsa.

2. Duk abin da zai haddasa rarrabuwar kai tsakanin muminai, to saɓon Allah ne, ya zama wajibi a nisance shi. Kamar yadda duk abin da zai taimaka wa haɗin kan muminai, wajibi ne a ƙarfafe shi.

3. Duk wani aiki ko da mai kyau ne , to mummunar niyya tana iya canza shi ya koma marar kyau, kamar yadda mugun nufin munafukai ya canza musu masallaci ya koma na cutarwa.

4. Yana daga cikin mafi munin ayyukan munafunci, mutum ya yi wani aiki a fili ya nuna da kyakkyawar niyya yake yi, to amma manufarsa ita ce ya cim ma wata mummunar buƙatarsa.

5. Faɗar Allah Ta'ala: "Da rarraba kawunan muminai." ta nuna cewa, babbar manufar haɗuwar Musulmi ita ce haɗin kai a tsakaninsu bisa biyayya ga Allah da Manzonsa (ﷺ).

6. Waɗanda suka gina masallaci kusa da wani masallacin don cutar da masu masallacin farko, sun aikata haramun, wajibi ne kuma a rushe wannan masallacin wanda aka gano mummunar manufar masu gina shi.

7. Aikin da aka gina shi a kan ikhlasi da koyi da Annabi (ﷺ) shi ne wanda aka gina a kan harsashin tsoron Allah da neman yardar Allah. Wanda kuwa aka gina shi a kan mugun nufi ko a kan bidi'a, to wannan shi ne wanda aka gina a kan gefen wani rami mai zabtarewa wanda zai rubta da mai shi cikin wutar Jahannama idan ya mutu a kai bai tuba ba.

8. Duk wanda ya yi wani gini don gudanar da wata ibada marar asali a shari'a a ciki, ko aikata kafirci da munafurci ko shirya abin da zai raba kan Musulmi, to wannan ma ya shiga cikin ma'nar masallacin cutarwa.

9. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son masu tsarkaka, wannan yana tabbatar da falalar kula da tsarkake jiki daga duk wata najasa, da tsarkake zuciya daga duk wani zunubi ko mummunan ƙuduri.

Suratut Tauba (107-110)

وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مَسۡجِدٗا ضِرَارٗا وَكُفۡرٗا وَتَفۡرِيقَۢا بَيۡنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَإِرۡصَادٗا لِّمَنۡ حَارَبَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ مِن قَبۡلُۚ وَلَيَحۡلِفُنَّ إِنۡ أَرَدۡنَآ إِلَّا ٱلۡحُسۡنَىٰۖ وَٱللَّهُ يَشۡهَدُ إِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ١٠٧ لَا تَقُمۡ فِيهِ أَبَدٗاۚ لَّمَسۡجِدٌ أُسِّسَ عَلَى ٱلتَّقۡوَىٰ مِنۡ أَوَّلِ يَوۡمٍ أَحَقُّ أَن تَقُومَ فِيهِۚ فِيهِ رِجَالٞ يُحِبُّونَ أَن يَتَطَهَّرُواْۚ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُطَّهِّرِينَ ١٠٨ أَفَمَنۡ أَسَّسَ بُنۡيَٰنَهُۥ عَلَىٰ تَقۡوَىٰ مِنَ ٱللَّهِ وَرِضۡوَٰنٍ خَيۡرٌ أَم مَّنۡ أَسَّسَ بُنۡيَٰنَهُۥ عَلَىٰ شَفَا جُرُفٍ هَارٖ فَٱنۡهَارَ بِهِۦ فِي نَارِ جَهَنَّمَۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٠٩ لَا يَزَالُ بُنۡيَٰنُهُمُ ٱلَّذِي بَنَوۡاْ رِيبَةٗ فِي قُلُوبِهِمۡ إِلَّآ أَن تَقَطَّعَ قُلُوبُهُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ١١٠وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مَسۡجِدٗا ضِرَارٗا وَكُفۡرٗا وَتَفۡرِيقَۢا بَيۡنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَإِرۡصَادٗا لِّمَنۡ حَارَبَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ مِن قَبۡلُۚ وَلَيَحۡلِفُنَّ إِنۡ أَرَدۡنَآ إِلَّا ٱلۡحُسۡنَىٰۖ وَٱللَّهُ يَشۡهَدُ إِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ١٠٧ لَا تَقُمۡ فِيهِ أَبَدٗاۚ لَّمَسۡجِدٌ أُسِّسَ عَلَى ٱلتَّقۡوَىٰ مِنۡ أَوَّلِ يَوۡمٍ أَحَقُّ أَن تَقُومَ فِيهِۚ فِيهِ رِجَالٞ يُحِبُّونَ أَن يَتَطَهَّرُواْۚ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُطَّهِّرِينَ ١٠٨ أَفَمَنۡ أَسَّسَ بُنۡيَٰنَهُۥ عَلَىٰ تَقۡوَىٰ مِنَ ٱللَّهِ وَرِضۡوَٰنٍ خَيۡرٌ أَم مَّنۡ أَسَّسَ بُنۡيَٰنَهُۥ عَلَىٰ شَفَا جُرُفٍ هَارٖ فَٱنۡهَارَ بِهِۦ فِي نَارِ جَهَنَّمَۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٠٩ لَا يَزَالُ بُنۡيَٰنُهُمُ ٱلَّذِي بَنَوۡاْ رِيبَةٗ فِي قُلُوبِهِمۡ إِلَّآ أَن تَقَطَّعَ قُلُوبُهُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ١١٠

107. Waɗanda kuwa suka gina masallaci don cutarwa da kafirci da rarraba kawunan muminai da kuma ba da mafaka ga wanda ya yaƙi Allah da Manzonsa tun da can. Kuma lalle za su rantse da Allah cewa ba su yi nufin komai ba sai abu mafi kyau, Allah kuwa Yana ba da shaidar cewa lalle su tabbas maƙaryata ne.

108. Kada ka yi salla a cikinsa har abada. Haƙiƙa masallacin da aka ɗora harsashinsa tun daga ranar farko a kan taƙawa shi ya cancanci ka yi salla a cikinsa. A cikinsa akwai wasu mazaje da suke so su tsarkaka. Allah kuwa Yana son masu tsarkaka.

109. Yanzu wanda ya sanya harhashin gininsa a kan taƙawa ga Allah da (neman) yardarsa shi ya fi ko kuwa wanda ya sanya harshashin gininsa a gefen rami mai zabtarewa, sai ya rubta da shi cikin wutar Jahannama? Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane azzalumai.

110. Ginin nasu da suka yi ba zai daina zama abin kokwanto a zukatansu ba har sai zukatan nasu sun tsittsinke. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin wasu munafukai ne da suka gina wani masallaci a Madina da nufin cutar da muminai domin su riƙa haɗuwa a cikinsa suna ƙulle-ƙullen sharri da makirci, da aikata kafirci da rarraba kan muminai da kuma bayar da mafaka ga wanda yake yaƙar Allah da Manzonsa tun kafin gina masallacin.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk da waɗannan munanan manufofin da suke da su waɗanda Allah ya fallasa su a kai, za su yi ta rantsuwa da Allah cewa ba su yi nufin komai ba sai kyautatawa. Amma Allah yana ba da shaidar cewa lalle su maƙaryata ne.
Ibnu Ishaƙa babban malamin Siran nan ya bayyana yadda wannan lamari ya kasance. Watau tun kafin Annabi (ﷺ) ya yi hijira zuwa Madina akwai wani mutum ɗan ƙabilar Khaza'atu mai suna Abu Amir Ar-Rahib wanda ya karɓi addinin Nasaranci. Yayin da Musulunci ya zo sai ya ƙi ba da gaskiya da shi. To bayan Manzon Allah (ﷺ) ya yi hijira zuwa Madina, Musulunci ya yaɗu ya kuma yi ƙarfi, sai Abu Amir ya gudu ya koma cikin Rumawa yana neman su taimaka masa don ya yaƙi Musulunci. Sannan ya koma Makka wajen kafiran Kuraishawa ya ci gaba da zuga su don su ci gaba da yaƙar Annabi (ﷺ) da sahabbansa, har zuwa lokacin da aka yi yaƙin Uhudu.
To bayan an ƙare yaƙin Uhudu Abu Amir ya ga yadda al'amarin Musulunci yake ƙara bunƙasa, sai ya gudu zuwa wurin Hiraƙla sarkin Rumawa yana neman taimakonsa a kan yaƙar Annabi (ﷺ), shi kuma ya yi masa alƙawarin taimakawa. Sai Abu Amir ya rubuto wa mutanensa munafukai, yana sanar da su cewa, ga shi nan tafe da rundunar mayaƙa da za su yaƙi Annabi su kuma ci nasara a kansa. Har ma ya umarce su da su gina masa wata mafaka inda jakadunsa za su riƙa kai-kawo kafin lokacin isowarsa ya yi. Saboda haka sai suka fara gina wani masallaci kusa da Masallacin Kuba. Bayan da suka gama ginin sai suka nemi Manzon Allah (ﷺ) kan ya zo ya albarkace shi da yin salla a cikinsa, suka kuma ce, wai sun gina shi ne saboda tsofaffi da raunana da masu wata larura su sami yin salla a cikinsa, musamman ma a lokacin sanyi. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ba su amsar cewa, ba zai samu damar yin salla ba a wannan lokacin, saboda yana kan hanyarsa ne ta zuwa yaƙin Tabuka, sai dai idan Allah ya dawo da shi da yardar Allah zai yi. To lokacin da Manzon Allah (ﷺ) yake komowa daga Tabuka ne wahayi ya zo masa yana ba shi labarin manufar gina wannan masallacin, wato an gina shi ne don cutar da addinin Musulunci da raba kawunan Musulmi da bayar da mafaka ga maƙiyansu. Sai Annabi (ﷺ) ya umarci Malik ɗan Dukhshum da Ma'anu ɗan Adiyyu da Wahshi da su je su rushe wannan masallaci. Suka kuma je suka cika aiki, suka ƙona shi ƙurmus, aka mayar da kufansa juji wurin zubar da shara, don kawai a wulaƙanta su tare da wannan mummunan aiki da suka yi. [Dubi, Ibn Kasir, *Tafsir*, Juzu'i na 2, Shafi na 388].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana Annabi (ﷺ) ya yi salla a masallacin munafukai a kowane lokaci, ya bayyana cewa, masallacin da aka ɗora harsashinsa a kan tsoron Allah tun daga ranar farko shi ya fi cancanta Annabi (ﷺ) ya yi salla a cikinsa, domin a cikinsa akwai wasu mazaje da suke son su tsarkaka daga kowace najasa da zunubi. Allah kuwa yana son masu tsarkaka.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na shiga wajen Manzon Allah (ﷺ) a ɗaya daga cikin gidajen matansa sai na ce: "Wane masallaci ne aka ɗora harsashinsa a kan tsoron Allah?"

Ya ce: Sai ya ɗebi tsakuwoyi a tafin hannunsa ya zubar da su ƙasa, sannan ya ce: “Shi ne wannan masallacin naku, wato masallacin Madina.” [Muslim #1398].

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ɗan ƙabilar Banu Khudra ya yi jayayya da wani ɗan ƙabilar Banu Amri ɗan Auf a kan ko wane masallaci ne aka sanya harsashinsa a kan tsoron Allah? Sai ɗan ƙabilar Banu Khudra ya ce, shi ne masallacin Manzon Allah (ﷺ), sai ɗayan ya ce shi ne masallacin Kuba. Sai suka je wajen Annabi (ﷺ) suka tambaye shi sai ya ce: “Shi ne wannan masallacin.” Yana nufin masallacinsa, sai kuma ya ce: “Wancan ma yana tattare da alheri mai yawa.” [Tirmizi #323, da Nasa’i #796, da Ahmad #11178].

Da yawa daga cikin malaman tafsiri suna ganin wannan ayar tana nufin masallacin Kuba ne. Wasu kuma cikinsu suna ganin tana nufin masallacin Manzon Allah ne. To amma ko da ta sauka ne a kan masallacin Kuba sai dai hukuncita ya haɗo har da masallacin Manzon Allah (ﷺ) domin shi ne ya fi cancanta a siffanta shi da wannan sifa.
Wasu malamai suna ganin ayar tana iya nufin duka masallatan biyu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba za a taɓa daidaita ginin da aka sanya harsashinsa a kan tsoron Allah da neman yardarsa da wanda aka sanya harsashin gininsa a gaɓar rami mai zaftarewa wanda yake gab da ya rufta da ginin da ke kansa, daga ƙarshe kuma ya rufta da wannan ginin da mai ginin cikin wutar Jahannama. Allah kuma ba ya shiryar da mutane azzalumai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan gini na masallacin bogi da nufin cutarwa da suka yi ya gadar musu da shakka da munafunci a zukatansu waɗanda ba za su gushe ba, har sai zukatan nasu sun tsuntsunke su mutu a kan haka. Allah kuwa Masani ne Mai hikima.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Waɗansu sun sayar da mafi tsadar abin da suka mallaka a duniya, wato rayukansu da dukiyoyinsu don su samu gidan Aljanna a lahira. Wasu kuwa sun sayar da mafi tsadar gidansu na lahira, wato Aljanna don su karɓi ɗan jin daɗi kaɗan na duniya. Waɗannan su ne hasararru na haƙiƙa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci siffofin muminai na kamala don kwaɗaitarwa a kan siffantuwa da irinsu.

3. Waɗannan siffofi guda tara da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata a nan suna daga cikin rassan imani.

4. Babban maƙasudin yin jihadi shi ne ɗaukaka kalmar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), addini kuma ya zamanto gaba ɗayansa na Allah ne. Mumini ba yana jihadi don biyan buƙatarsa ta kansa ba ne, don haka ne musibar da take samun mai jihadi a rayuwarsa ko dukiyarsa ladansa yake wajen Allah, shi ne mai biyan sa, domin ya riga ya sayi rayukan muminai da dukiyoyinsu don ya biya su da gidan Aljanna.

5. Babu wani ciniki da aka taɓa yi da ya kai darajar wannan ciniki, domin mai sayen shi ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka); abin sayen su ne rayukan muminai da dukiyoyinsu; abin da za a biya su da shi kuwa shi ne Aljannar ni’ima; wanda cinikin ya gudana a hannunsa kuwa shi ne mafificin manzannin Allah Annabi Muhammadu (ﷺ); littafin da aka rubuta cinikin a cikinsa kuma shi ne mafi darajar littattafan Allah, wato Alƙur’ani mai girma. Lalle wannan shi ne babban rabo.

6. Wanda duk ya yi ƙoƙari wajen bin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to haƙiƙa ya sayar da rayuwarsa ga Allah, ya kuma ‘yanta kansa daga azabar Allah.

7. Mai tuba dole ne ya himmatu da ayyukan ƙwarai kamar ibada da yin umarni da kyakkyawan abu da hana mummuna.

8. A cikin aya ta 112 Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗi siffofi tara, shida na farko suna da alaƙa ne da mahalicci, sifa ta bakwai da ta takwas kuwa suna da alaƙa ne da mu'amala da mahluƙi, siffar ƙarshe ta tara ta ƙunshi ɓangarorin biyu gaba ɗaya.

Suratut Tauba (111-112)

*إِنَّ ٱللَّهَ ٱشۡتَرَىٰ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَنفُسَهُمۡ وَأَمۡوَٰلَهُم بِأَنَّ لَهُمُ ٱلۡجَنَّةَۚ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَيَقۡتُلُونَ وَيُقۡتَلُونَۖ وَعۡدًا عَلَيۡهِ حَقّٗا فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَٱلۡإِنجِيلِ وَٱلۡقُرۡءَانِۚ وَمَنۡ أَوۡفَىٰ بِعَهۡدِهِۦ مِنَ ٱللَّهِۚ فَٱسۡتَبۡشِرُواْ بِبَيۡعِكُمُ ٱلَّذِي بَايَعۡتُم بِهِۦۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١١١ ٱلتَّٰٓئِبُونَ ٱلۡعَٰبِدُونَ ٱلۡحَٰمِدُونَ ٱلسَّٰٓئِحُونَ ٱلرَّٰكِعُونَ ٱلسَّٰجِدُونَ ٱلۡأٓمِرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَٱلنَّاهُونَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَٱلۡحَٰفِظُونَ لِحُدُودِ ٱللَّهِۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١١٢

111. Lalle Allah Ya sayi rayuka da dukiyoyin muminai daga wurinsu cewa suna da Aljanna: Za su yi yaƙi saboda Allah, sai su kashe su ma kuma a kashe su. Alƙawari ne na gaskiya da Ya ɗaukar wa kansa a cikin Attaura da Linjila da Alƙur'ani. Wane ne ya fi Allah cika alƙawarinsa? Saboda haka sai ku yi farin ciki da cinikin nan naku da kuka yi da Shi. Wannan kuwa shi ne rabo mai girma.

112. Masu tuba, masu bauta, masu godiya, masu azumi, masu ruku'i, masu sujjada, masu yin umarni da aikin alheri masu kuma hani ga mummunan aiki, da masu kiyaye iyakokin Allah. To sai ka yi wa muminai (masu irin waɗannan siffofin) albishir.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin cewa, ya yi wani babban ciniki tsakaninsa da muminai, inda ya ce ya sayi rayukansu da dukiyoyinsu daga wurinsu, ya kuma sanya Aljanna ita ce farashin biyansu, a kan za su yi yaƙi don ɗaukaka kalmar Allah, ko su kashe kafirai ko kuma su a kashe su, to tabbas Aljanna ta wajaba gare su, wannan alƙawari ne na Allah tabbatacce a cikin littafin Attaura da Linjila da Alƙur'ani. Babu kuwa wanda ya fi Allah kyan cika alƙawari.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai masu jihadi da su yi farin ciki da wannan ciniki da suka ƙulla da Allah, wannan kuma shi ne babban rabo.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta muminai waɗanda ya sayi rayukansu da dukiyoyinsu daga wurinsu da cewa, su ne masu tuba daga saɓon Allah, masu bautar Allah cikin ƙauna da ƙaskantar da kai, masu yabo da godiya ga Allah a kowane hali nasu, masu yin azumi, masu salla suna ruku'i da sujjada a sallolinsu na farilla da na nafila, masu yin umarni da kyakkyawan aiki, wato abin da Allah da Manzonsa suke umarni da shi na imani da Allah da ayyuka na ƙwarai, suna kuma hana mummunan aiki, watau duk abin da Allah da Manzonsa (ﷺ) suka hana, masu kiyaye iyakokin Allah, suna aiki da umarninsa da haninsa, ba sa tozarta wani hukunci na cikin shari'ar Allah. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da cewa ya yi wa waɗannan muminai albishir da samun duk wani alheri na duniya da na lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Aƙida ita ce igiya mai ƙarfi da take ƙulla alaƙa tsakanin mutane. Idan igiyar aƙida ta tsinke, to duk sauran igiyoyin alaƙoƙi sun tsinke, don haka alaƙar dangantaka ko surukutaka ko ƙabila ko ƙasa ba za su yi wani amfani ba tsakanin mutum da mutum.

2. Haramun ne Musulmi ya nema wa kafiri gafarar Allah ko rahamarsa, yana da rai ko bayan ya mutu.

3. Nema wa wani gafara ba zai amfane shi da komai ba sai idan yana da imani.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya kama bayinsa da wani laifi sai bayan ya bayyana musu hukuncin wannan laifin. Don haka hankali shi kaɗai ba zai isa a yanke wa mutum hukunci da shi ba ba tare da wahayi ba.

5. Idan aka keta alfarmar dokokin Allah aka auka wa saɓon Allah, to wannan sababi ne da kan jawo wa mutane ɓacewa daga kan hanyar shiriya.

Suratut Tauba (113-116)

مَا كَانَ لِلنَّبِيِّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن يَسۡتَغۡفِرُواْ لِلۡمُشۡرِكِينَ وَلَوۡ كَانُوٓاْ أُوْلِي قُرۡبَىٰ مِنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمۡ أَنَّهُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ١١٣ وَمَا كَانَ ٱسۡتِغۡفَارُ إِبۡرَٰهِيمَ لِأَبِيهِ إِلَّا عَن مَّوۡعِدَةٖ وَعَدَهَآ إِيَّاهُ فَلَمَّا تَبَيَّنَ لَهُۥٓ أَنَّهُۥ عَدُوّٞ لِّلَّهِ تَبَرَّأَ مِنۡهُۚ إِنَّ إِبۡرَٰهِيمَ لَأَوَّٰهٌ حَلِيمٞ ١١٤ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُضِلَّ قَوۡمَۢا بَعۡدَ إِذۡ هَدَىٰهُمۡ حَتَّىٰ يُبَيِّنَ لَهُم مَّا يَتَّقُونَۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٌ ١١٥ إِنَّ ٱللَّهَ لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۚ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٖ ١١٦

113. Bai kamata ba ga Annabi da waɗanda suka yi imani su nema wa mushrikai gafara, ko da kuwa sun kasance dangi ne na kusa, bayan kuwa ya riga ya bayyana gare su cewa lalle su ‘yan wuta ne.

114. Neman gafarar Ibrahimu kuwa ga babansa bai kasance ba sai don kawai alƙawarin da ya yi masa ne. To lokacin da ya bayyana gare shi cewa shi maƙiyin Allah ne sai ya nesanta kansa da shi. Lalle Ibrahimu ya tabbata mai yawan bautar Allah ne, mai haƙuri.

115. Allah kuwa ba zai taɓa ɓatar da wasu mutane ba bayan Ya riga Ya shiryar da su, har sai Ya bayyana musu abin da za su kiyaye. Lalle Allah Masanin komai ne.

116. Lalle Allah Shi ne Mai mulkin sammai da ƙasa, Yana rayawa kuma Yana kashewa. Ba ku da wani majiɓincin lamarinku in ban da Allah, ba ku kuma da wani mai taimako.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana hukuncin nema wa waɗanda suka mutu a kan shirka gafarar Allah, ya bayyana cewa, bai dace ba ga Annabi (ﷺ) da muminai su nema wa mushirikai gafarar Allah ko da kuwa sun kasance dangi ne na kusa, bayan sun gane cewa su ‘yan wuta ne domin sun mutu suna kafirci ba su tuba ba.
Sai Allah Ta’ala ya bayyana cewa, neman gafarar da Annabi Ibrahimu ya yi wa mahaifinsa, ya yi shi ne kawai don alƙwarin da ya ɗaukar masa na cewa zai nema masa gafarar Allah, kamar yadda ya zo a cikin *Suratu Maryam*, aya ta 47. To amma lokacin da Annabi Ibrahimu ya tabbatar da cewa mahaifin nasa maƙiyin Allah ne sai ya nesanta kansa daga gare shi. Lalle Annabi Ibrahimu mai yawan ƙaskantar da kansa ne ga Allah da yawan roƙon Allah, zuciyarsa kuma na cike da tsoro da fata, kuma mai yawan juriya ne da haƙuri a kan duk abin da ake yi masa na musgunawa.

An karɓo daga Sa’idu ɗan Musayyab shi kuma daga mahaifinsa ya ce: Lokacin da Abu Ɗalibi yake dab da barin duniya, Manzon Allah (ﷺ) ya je wajensa, sai ya samu Abu Jahlin da Abdullahi ɗan Abu Umayya a wurinsa, sai ya ce da shi: “Baffa, ka ce: Babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah. Da wannan kalmar ne zan yi maka shaida a wurin Allah.” Sai Abu Jahlin da Abdullahi ɗan Abu Umayyata suka ce masa: “Ya Abu

Ɗalibi, yanzu ashe za ka guji tafarkin Abdulmuɗɗalib?" Annabi (ﷺ) ya ci gaba da bijirar masa da Kalmar Shahada, su kuma suna ci gaba da nanata masa waccan maganar har daga ƙarshe dai Abu Ɗalibi ya ce shi yana nan a kan tafarkin Abdulmuɗɗalib, ya ƙi karɓar Kalmar Shahada. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle zan nema maka gafara muddin dai ba a hana ni ba." To a sannan ne wannan ayar ta sauka. [Bukhari #3884, da Muslim #24].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ba zai ɓatar da wasu mutane ba bayan ya shiryar da su sun yi imani, har sai ya bayyana musu abin da ya wajaba a kansu su kiyaye. Lalle kuwa Allah masanin komai ne.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ba da labarin cewa, lalle shi ne kaɗai mai mulkin sammai da ƙasa, yana rayawa yana kashewa, kuma mutane ba su da wani majiɓincin al'amarinsu wanda zai amfanar da su in ban da shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne kuma kaɗai mai taimakon su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar sahabban Annabi (ﷺ) da girman martabarsu a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), Allah ya tabbatar da cewa ya yafe ma duk waɗanda suka fita yaƙin Tabuka tare da Manzon Allah (ﷺ) waɗanda adadinsu ya kai mutum dubu talatin. Don haka ci gaba da sukar wasu daga cikin waɗannan bayin Allah da zargin su da wasu laifuka suka ne ga wannan shaida ta yafiya da Allah ya ba su.

2. Duk wani mumini yana da buƙatar tuba zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kamar yadda Annabi (ﷺ) da muhajirai da mutanen Madina (Al-Ansar) suka buƙaci tuba zuwa ga Allah duk da girman matsayinsu a wurin Allah.

3. Duk wata ibada mai wahala to tana da wani girman falala a wurin Allah gwargwadon wahalar da ke cikinta.

4. Alamun dacewa da alheri shi ne lokacin da zuciyar bawa ta rataya da Ubangiji cikakkiyar rataya, ta kauce wa ƙwallafa rai ga wani mahaluƙi ba Allah ba.

5. Muhimmancin gaskiya da amfaninta ga bawa.

6. Haƙƙi ne a kan duk wanda ya fahimci Allah da girmansa, ya lizimci gaskiya cikin maganganunsa da ayyukansa.

7. Lazimtar masu gaskiya da shiga cikin ƙungiyarsu ba ya yiwuwa sai ga mai taƙawa, wato mai kiyaye dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratut Tauba (117-119)

لَّقَد تَّابَ ٱللَّهُ عَلَى ٱلنَّبِيِّ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ فِي سَاعَةِ ٱلۡعُسۡرَةِ مِنۢ بَعۡدِ مَا كَادَ يَزِيغُ قُلُوبُ فَرِيقٖ مِّنۡهُمۡ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّهُۥ بِهِمۡ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ١١٧ وَعَلَى ٱلثَّلَٰثَةِ ٱلَّذِينَ خُلِّفُواْ حَتَّىٰٓ إِذَا ضَاقَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَرۡضُ بِمَا رَحُبَتۡ وَضَاقَتۡ عَلَيۡهِمۡ أَنفُسُهُمۡ وَظَنُّوٓاْ أَن لَّا مَلۡجَأَ مِنَ ٱللَّهِ إِلَّآ إِلَيۡهِ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡ لِيَتُوبُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ١١٨ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَكُونُواْ مَعَ ٱلصَّٰدِقِينَ ١١٩

117. Tabbas haƙiƙa Allah Ya yafe wa Annabi da masu hijira da kuma Ansaru waɗanda suka bi shi a lokacin tsanani bayan har zukatan wasu ƙungiyoyi daga cikinsu sun kusa su karkace, sannan (Allah) Ya karɓi tubansu. Lalle Shi Mai tausasawa ne, Mai jin ƙai a gare su
118. Kuma (Ya yafe wa) mutanen nan guda uku waɗanda aka dakatar da karɓar tubansu, har sai yayin da duniya ta yi musu ƙunci duk da yalwarta, kuma zukatansu suka ƙuntata, suka tabbatar da cewa dai babu wata mafaka daga Allah sai dai a wajensa. Sannan sai Ya yi musu muwafaƙar tuba don su tuba. Lalle Allah Shi ne Mai yawan karɓar tuba, Mai jin ƙai.

119. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah kuma ku zama tare da masu gaskiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da batun waɗanda suka fita yaƙin Tabuka tare da Manzon Allah (ﷺ) da waɗanda suka ƙi fita ba tare da wata lalura ba, sannan su kuma ba munafukai ne ba; Shaiɗan ne kawai ya ribace su ya hana su bin Manzon Allah (ﷺ).
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labari cewa, ya yafe wa Annabi da waɗanda suka yi hijira da mutanen Madina waɗanda suka fita tare da shi zuwa yaƙin Tabuka a lokacin da ake tsananin zafin rana ga kuma tafiya mai nisa sannan ga ƙarancin guzuri da abin hawa. Haƙiƙa Allah ya yafe musu bayan zukatan wasu sahabbai sun kusa su kauce wa gaskiya, to amma sai ya karɓi tubarsu. Lalle Allah mai tausaya musu ne mai jin ƙan su.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) game da labarin Rundunar Tsanani (mayaƙan da suka fita yaƙin Tabuka) sai ya ce: “Mun fita tare da Manzon Allah (ﷺ) cikin tsananin zafi zuwa Tabuka sai muka sauka wani masauki inda muka haɗu da ƙishirwa mai tsanani, har sai da muka riƙa tsammanin wuyoyinmu za su tsinke, har ta kai mutum zai fita neman ruwa ba zai dawo ba sai yana jin kamar wuyansa zai tsinke. Har sai da ta kai mutum zai yanka raƙuminsa ya tatse tumbinsa don ya samu ruwan da zai sha. Sai Abubakar ya ce: “Ya Manzon Allah (ﷺ), Allah ya saba da yi maka alheri idan ka roƙe shi, to ka roƙa mana Allah.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kana son hakan?” Sai ya ce: “E.” Sai ya ɗaga hannayensa yana addu’a, bai saukar da su ba har sai da hadari ya gangamo sama ta kece da ruwa. Sahabbai suka cika abubuwan da ke tare da su, sannan muka dawo muna duba sama sai muka ga hadarin bai wuce wannan rundunar tamu ba.” [Ibnu Khuzaima #101, da Ibnu Hibban #1383].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya karɓi tuban wasu sahabbai waɗanda suka ƙi fita yaƙin Tabuka tare da Manzon Allah (ﷺ) ba tare da wani dalili ba, wato Ka’abu ɗan Maliki da Muraratu ɗan Rabi’atu Al-Amiri da Hilalu ɗan Umayyata Al-Waƙifi. Bayan dawowar Manzon Allah (ﷺ) garin Madina, munafukai suka yi ta zuwa wurinsa suna bayyana masa uzururrukan ƙarya, yana karɓa yana nema musu gafarar Allah, to amma su waɗannan ukun suka ƙi yarda su yi masa ƙarya, suka fito fili suka faɗa masa gaskiya cewa ba su da wani dalilin da ya hana su fita yaƙi tare da shi, sai dai kawai ruɗin Shaiɗan. Annabi (ﷺ) ya umarci sahabbai da su ƙaurace musu har sai Allah ya saukar da hukunci a kansu, su ma daga ƙarshe ya umarci matansu da su ƙaurace musu, suka kuwa ƙaurace musu, sai matar Hilalu ce kaɗai ta nemi alfarmar Annabi (ﷺ) a kan ya yi mata izini ta zauna tare da shi tana yi masa hidima saboda kasancewarsa tsoho ne yana buƙatar wani tare da shi, Annabi (ﷺ) ya yi mata izini amma ya faɗa mata cewa kada ta yarda ya kusance ta. Saboda haka suka zauna cikin ƙunci da wahalar rayuwa lokaci mai tsawo, duniya kuma ta yi musu zafi, suka rasa inda za su sa kansu; suka tabbatar da cewa babu wata mafaka sai dai wurin Allah, saboda haka suka koma gare shi suna neman gafara da afuwa game da laifin da suka aikata. [Dubi, Bukhari #4418, da Muslim #2769].
Bayan waɗannan sahabbai su uku sun kwana hamsin a cikin wannan hali mawuyaci, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dube su da rahamarsa da afuwarsa ya yi musu katari ya karɓi tubansu, ya saukar da waɗannan ayoyi inda ya bayyana cewa, ya yafe wa sahabban nan guda uku waɗanda Annabi (ﷺ) ya

dakatar da hukunci a kansu har sai Allah ya yi hukunci a kansu, har lokacin da duniya ta yi musu ƙunci duk kuwa da yalwarta, kuma zukatansu suka ƙuntata gare su, saboda abin da suke ciki na baƙin ciki da damuwa da tashin hankali; suka tabbatar da cewa dai babu wata mafaka da za su fake a wurinta sai Allah, sai Allah ya musu gamon-katar da samun tuba, suka tuba Allah ya karɓi tubansu don su koma su ci gaba da bin umarninsa. Lalle Allah mai yawan karɓar tuba ne mai jin ƙai.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai gaba ɗaya da su kiyaye dokokinsa kuma a koyaushe su kasance tare da masu gaskiya.

An karɓo daga Ka'abu ɗan Malik ya ce: Lokacin da ayoyin yafiya gare su suka sauka ya zo gaban Manzon Allah (ﷺ) ya zauna ya ce: "Yana daga cikin tuban da zan yi in bayar da dukiyata gaba ɗayanta ga Allah da Manzonsa." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce da shi: "Ka riƙe wani ɓangare na dukiyarka ya fi maka alheri." Sai ya ce: "To zan riƙe kaso na Khaibar." Ya kuma ce: "Ya Manzon Allah, Allah ya tserar da ni ne kawai saboda faɗar gaskiya da na yi, to yana daga sharaɗin tubana cewa ba zan ƙara faɗar abin da ba gaskiya ba har abada." Ya ce: "Na rantse da Allah, babu wani Musulmin da Allah ya jarrabe shi a kan faɗar gaskiya tun lokacin da na faɗa wa Manzon Allah abin da na faɗa masa har zuwa yau ɗin nan da irin kyakkyawar jarraba da ya yi min. Wallahi ban ƙara yin ƙarya da gangan ba tun lokacin da na faɗa wa Manzon Allah (ﷺ) wannan magana har zuwa yau. Ina kuma roƙon Allah ya ci gaba da tsare ni a cikin abin da ya yi saura na rayuwata." [Dubi, Bukhari #4418, da Muslim #2769].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya nufi biyayya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to tsayuwarsa da zamansa da tafiyarsa da motsinsa da natsuwarsa dukansu za a rubuta masa su a matsayin ayyukan ƙwarai da zai ci moriyarsu a wurin Allah.

2. Kaunar Annabi (ﷺ) tana gaba da komai har ma da ran mumini. Don haka zai iya fansar Manzon Allah (ﷺ) da rayuwarsa da duk abin da ya mallaka.

3. Duk wani abu da zai yi wa rai raɗaɗi ya wahalar da shi, to yana zama kaffarar zunubai ko da kuwa ba ɗan'adam ne yake jawo wa kansa shi ba, kamar rashin lafiya da makamantanta, amma wahalar da za ta samu mutum a dalilin biyayya ga Allah, to za a rubuta masa lada a kai, a kuma ɗaga darajarsa.

Suratut Tauba (120-121)

مَا كَانَ لِأَهۡلِ ٱلۡمَدِينَةِ وَمَنۡ حَوۡلَهُم مِّنَ ٱلۡأَعۡرَابِ أَن يَتَخَلَّفُواْ عَن رَّسُولِ ٱللَّهِ وَلَا يَرۡغَبُواْ بِأَنفُسِهِمۡ عَن نَّفۡسِهِۦۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ لَا يُصِيبُهُمۡ ظَمَأٞ وَلَا نَصَبٞ وَلَا مَخۡمَصَةٞ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا يَطَـُٔونَ مَوۡطِئٗا يَغِيظُ ٱلۡكُفَّارَ وَلَا يَنَالُونَ مِنۡ عَدُوّٖ نَّيۡلًا إِلَّا كُتِبَ لَهُم بِهِۦ عَمَلٞ صَٰلِحٌۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٢٠ وَلَا يُنفِقُونَ نَفَقَةٗ صَغِيرَةٗ وَلَا كَبِيرَةٗ وَلَا يَقۡطَعُونَ وَادِيًا إِلَّا كُتِبَ لَهُمۡ لِيَجۡزِيَهُمُ ٱللَّهُ أَحۡسَنَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٢١

120. Bai kamata ba ga mutanen Madina da waɗanda suke kewaye da su daga mazauna ƙauye su noƙe su ƙi bin Manzon Allah, ko kuma su zaɓi kansu fiye da shi. Wannan kuwa saboda ba wata ƙishirwa ko wahala ko yunwa da za ta same su a kan hanyar Allah, kuma ba za su taka wani wuri ba da zai ɓata wa kafirai rai, kuma ba za su tafka wa abokan gaba wata hasara ba sai an rubuta musu lada saboda shi (wato kowane ɗaya daga abubuwan da aka zana). Lalle Allah ba Ya tozarta ladan masu kyautatawa.

121. Ba kuma za su bayar da wata sadaka ba, ƙarama ko kuma babba, kuma ba wani kwazazzabo da za su keta sai an rubuta musu ladansu don Allah Ya saka musu da mafi kyawun abin da suka zamanto suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa bai dace ba ga mutanen Madina da mazaunan ƙauyukan da ke zagaye da su su noƙe su ƙi fita tare da Manzon Allah (ﷺ) zuwa yaƙin Tabuka ko kuma su fifita kansu a kansa, su zaɓi su huta shi kuma yana cikin wahala, wannan bai dace da su ba. Saboda ba wata ƙishirwa ko wahala ko yunwa mai tsanani da za su same su a kan hanyar Allah, kuma ƙafafunsu ba za su taka wata ƙasa ba da wannan zai zama musabbabin ɓata wa kafirai rai, kuma ba za su tafka wa maƙiyansu wata asara ba ta kisa ko cinye su da yaƙi ko makamancin haka, face sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rubuta musu kyakkyawan sakamako saboda wannan, lalle Allah ba ya tozarta ladan masu kyautatawa.
Hakanan ba za su bayar da wata sadaka ba ƙarama ko babba, kuma ba wani kwari da za su haye yayin fitarsu yaƙi, face sai an rubuta musu ladansa, don Allah ya saka musu da mafi kyan ayyukan da suka zamanto suna aikatawa.

An karɓo daga Abdurrahman ɗan Jabrin ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Dugadugan bawa ba za su yi ƙura a kan hanyar Allah ba sannan kuma wuta ta shafe shi.” [Bukhari #2811].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar neman ilimin addini da muhimmancinsa.

2. Wanda duk ya yi ilimi, to ya kamata ya yaɗa shi cikin mutane, ya karantar da waɗanda ba su sani ba, ya yi musu nasiha da faɗakarwa.

3. Lalle manufar mai neman ilimi ya wajaba ya zamanto ita ce sanin addinin Allah, da sanar da shi da kira zuwa ga gaskiya. Bai halatta mutum ya nemi ilimi don ya yi wa mutane girman kai ko ya wulaƙanta su ko don neman duniya kawai ba.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da a fara yaƙar abokan gaba kafirai na kusa saboda dalilai kamar haka:
• Idan akwai masu barazana ga Musulmi na nesa da na kusa, kuma ba zai yiwu a tinkare su gaba ɗaya a lokaci guda ba, to lalle ya kamata a fara da na kusa.
• Farawa da na kusa shi ya fi, domin abin da za a buƙata na abin hawa da guzuri ba zai yi yawa ba.
• Idan sojojin Musulmi suka ƙetare abokan gabarsu na kusa, suka fuskanci na nesa, to sun jefa ƙasarsu da ‘ya’yansu da matansu cikin hatsari.
• Maƙiyan Musulmi masu maƙotaka da su, ko dai su kasance ƙarfafa ne ko kuma raunana, to idan sun kasance ƙarfafa ne, to babu shakka haɗarinsu babba ne a kan Musulmi fiye da waɗanda suke nesa; idan kuwa sun zamanto masu rauni ne, to cikin sauƙi Musulmi za su yi nasara a kansu, wannan kuma sai ya ƙara musu kwarjini da ban-tsoro a zukatan maƙiyansu na nesa.

5. Mumini na ƙwarai kamar yadda zai zamanto mai tsananta wa abokan gabarsa, to haka ya wajaba ya zamanto mai tausasawa ga ɗan’uwansa mumini.

6. Koyaushe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana kwaɗaitarwa a kan tsoron sa da kiyaye dokokinsa, domin da haka ake samun nasara a kan maƙiya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi alƙawari cewa, yana

tare da masu taƙawa; duk kuwa wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake tare da shi, to ba za a yi galaba a kansa ba har abada.

Suratut Tauba (122-123)

*وَمَا كَانَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لِيَنفِرُواْ كَآفَّةٗۚ فَلَوۡلَا نَفَرَ مِن كُلِّ فِرۡقَةٖ مِّنۡهُمۡ طَآئِفَةٞ لِّيَتَفَقَّهُواْ فِي ٱلدِّينِ وَلِيُنذِرُواْ قَوۡمَهُمۡ إِذَا رَجَعُوٓاْ إِلَيۡهِمۡ لَعَلَّهُمۡ يَحۡذَرُونَ ١٢٢ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَٰتِلُواْ ٱلَّذِينَ يَلُونَكُم مِّنَ ٱلۡكُفَّارِ وَلۡيَجِدُواْ فِيكُمۡ غِلۡظَةٗۚ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلۡمُتَّقِينَ ١٢٣

122. Bai kamata muminai su fita yaƙi gaba ɗaya ba. Me zai hana wasu jama'a daga kowace ƙabila (su zauna) don su koyi ilimin addini, su kuma yi wa mutanensu gargaɗi idan sun dawo musu don su kiyaye (dokokin Allah)?.

123. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yaƙi kafirai waɗanda suke maƙota da ku, kuma su sami kausasawa daga wajenku. Ku kuma sani cewa Allah Yana tare da masu taƙawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, bai kamata ga muminai su fita wajen yaƙi gaba ɗayansu ba a lokaci guda. Me zai hana a cikin kowace ƙabila a sami wata jama'a da su ne za su fita yaƙi, wasu kuma su zauna don su karanci ilimi na addinin Allah don su yi karantarwa da gargaɗi ga waɗanda suka fita yaƙi idan sun dawo gare su, ko sa kiyaye abin da zai jawo musu fushin Allah da azabarsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su yaƙi kafiran da suke kusa da garuruwansu, kuma su tsananta musu wajen yaƙi, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa yana tare da masu taƙawa, wato masu kiyaye dokokin Allah a cikin komai har da sha'anin jihadi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ya kamata a koyaushe mumini ya riƙa bincikar imaninsa yana jaddada shi, domin ya riƙa hauhawa koyaushe.

2. Zukata suna kamuwa da rashin lafiya ta kafirci da munafurci ko kuma da wasu miyagun halaye.

3. Wannan ayar ta 124 tana tabbatar da aƙidar Ahalussunna mai cewa, imani yana ƙaruwa kuma yana raguwa.

4. Yana daga cikin manyan makaman bayin Allah na ƙwarai, samun sanin Allah da Manzonsa da farin ciki da hakan da yin imani Allah da aiki da Alƙur'ani da sunnar Manzon Allah (ﷺ).

Suratut Tauba (124-127)

وَإِذَا مَآ أُنزِلَتۡ سُورَةٞ فَمِنۡهُم مَّن يَقُولُ أَيُّكُمۡ زَادَتۡهُ هَٰذِهِۦٓ إِيمَٰنٗاۚ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَزَادَتۡهُمۡ إِيمَٰنٗا وَهُمۡ يَسۡتَبۡشِرُونَ ١٢٤ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ فَزَادَتۡهُمۡ رِجۡسًا إِلَىٰ رِجۡسِهِمۡ وَمَاتُواْ وَهُمۡ كَٰفِرُونَ ١٢٥ أَوَلَا يَرَوۡنَ أَنَّهُمۡ يُفۡتَنُونَ فِي كُلِّ عَامٖ مَّرَّةً أَوۡ مَرَّتَيۡنِ ثُمَّ لَا يَتُوبُونَ وَلَا هُمۡ يَذَّكَّرُونَ ١٢٦ وَإِذَا مَآ أُنزِلَتۡ سُورَةٞ نَّظَرَ بَعۡضُهُمۡ إِلَىٰ بَعۡضٍ هَلۡ يَرَىٰكُم مِّنۡ أَحَدٖ ثُمَّ ٱنصَرَفُواْۚ صَرَفَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُم بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَفۡقَهُونَ ١٢٧

124. Idan kuwa aka saukar da wata sura, daga cikinsu akwai waɗanda suke cewa: “Wane ne daga cikinku wannan ta ƙara masa imani?” To amma waɗanda suka yi imani su kam ta ƙara musu imani alhali suna cike da farin ciki.

125. Amma kuma waɗanda suke da munafunci a zukatansu sai (surar) ta ƙara musu wata dauɗa a kan dauɗarsu (ta munafunci) suka kuma mutu suna kafirai.

126. Shin yanzu ba sa ganin cewa ana jarrabar su a kowace shekara sau ɗaya ko sau biyu, sannan ba sa tuba kuma ba sa wa’azantuwa?
127. Idan kuma an saukar da wata surar sai su kalli junansu (su ce): “Shin akwai wani mai ganin ku?” Sannan sai su juya. To Allah Ya juyar da zukatansu saboda su mutane ne da ba sa fahimta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin cewa, idan ya saukar wa Annabi (ﷺ) wata sura ta Alƙur’ani, sai wasu daga cikin munafukai su riƙa ce wa juna: “Wane ne daga cikinku wannan surar ta ƙara masa imani?” Suna kuma faɗar haka cikin izgili da gatse da reni ga Alƙur’ani. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, wannan surar tana ƙara wa muminai imaninsu domin za su rungumi abin da ta zo da shi na umarni da hani kuma za su yi aiki da su kuma imaninsu zai ƙaru, suna kuma masu farin ciki da hakan. Amma waɗanda munafinci ya lulluɓe zukatansu, sai surar ta ƙara musu kafirci da shakka a kan kafircinsu da shakkarsu ta farko, su kuma mutu suna kafirai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shin yanzu su waɗannan munafukan ba sa ganin a duk shekara sai an jarrabe su sau ɗaya ko sau biyu, sannan ba sa tuba kuma ba sa wa’azantuwa? Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa, idan ya saukar da wata sura wadda take fallasa asirin munafikai sai su kalli junansu su ce: “Shin ko akwai mai ganin ku wanda zai kai wa Muhammadu labarinku asirinmu ya tonu a wurinsa?” To daga nan sai su juya wa wannan surar baya, su ƙi ba da gaskiya da ita ko su yi aiki da ita, tare da cewa Alƙur’ani ya tona asiransu, amma wannan bai sa su sun shiryu ba, sai Allah ya juyar da zukatansu saboda sun zamanto mutane ne da ba sa fahimtar littafin Allah, suna nuna girman kai da bijire wa aiki da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi (ﷺ) mutum ne da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zaɓo shi daga jinsin al’ummar Larabawa.

2. Ishara zuwa ga falalar Larabawa, domin kasancewar Annabi (ﷺ) daga jinsinsu, da ɗaga kuma martabar Kuraishawa domin zamantowarsa ɗan ƙabilarsu, sannan da girman darajar gidan Banu Hashim domin daga nan ne Annabi (ﷺ) ya fito. [Dubi, Muslim #2276].

3. Tausayin Annabi (ﷺ) ga al’ummarsa, don haka duk wani abu da zai wahalar da al’ummarsa yana damun sa, yana kuma kwaɗayin shiriyarsu da kuɓutarsu ranar alƙiyama.

4. Duk wani ƙarfi da mulki yana tuƙewa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka wanda ya riƙe shi ya isar masa komai duniya da lahira.

5. Wajibi ne duk wani mumini ya dogara ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai, musamman mai kira zuwa ga Allah, domin wannan shi ne kariyarsa daga duk masu ƙoƙarin cutar da shi ko wulaƙanta shi.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne Ubangijin Al’arshi kuma Al’arshinsa mai girma ne. Wannan ishara ce a kan gamammen mulkin Allah ga sauran halittu waɗanda ba su kai Al’arshi girma ba.

Suratut Tauba (128-129)

لَقَدۡ جَآءَكُمۡ رَسُولٞ مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ عَزِيزٌ عَلَيۡهِ مَا عَنِتُّمۡ حَرِيصٌ عَلَيۡكُم بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ١٢٨ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقُلۡ حَسۡبِيَ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُۖ وَهُوَ رَبُّ ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡعَظِيمِ ١٢٩

128. Haƙiƙa Manzo ya zo muku daga jinsinku; abin da zai wahalar da ku yana damun sa; mai kwaɗayin alheri ne gare ku, mai tausayawa kuma mai jin ƙai ga muminai.

129. To idan sun ba da baya sai ka ce: “Allah Ya ishe ni, babu wani abin bautawa da gaskiya sai Shi, a gare Shi kaɗai na dogara; kuma Shi ne Ubangijin Al’arshi mai girma.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da Larabawa cewa, wani Manzo daga cikinsu ya zo musu; shi ne Annabi Muhammadu (ﷺ). Daga siffofinsa ya kasance duk wani abu da zai wahalar da su yana yi masa girma, wato yana damun sa, sannan shi mai kwaɗayin shiriyarsu ne da isar musu da alheri, kuma shi mai tausayi ne da jin ƙai ga muminai.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Manzon Allah (ﷺ) ya bar mu, babu wani tsuntsu da yake jujjuya fukafukansa a cikin iska, face sai da ya ba mu wani ilimi a kansa.” Ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Babu wani abu wanda zai kusantar da ku ga Aljanna ya kuma nisanta ku daga wuta, face an yi muku bayaninsa.” [Ɗabarani #1647].

An karɓo daga Abu Hurairata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Misalin zamana da al’ummata shi ne kawai kamar wani mutum da ya hura wuta, sai ƙwarin nan faɗa-wuta suka riƙa faɗawa cikinta, to haka ni ma nake riƙe kwankwasonsu ina hana su amma suna kutsa kansu suna faɗawa cikin wutar.” [Bukhari #6483, da Muslim #2284].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fuskantar da bayaninsa ga Manzon Allah (ﷺ) cewa, idan sun bijire sun ƙi yin imani da shi sun ƙi yi masa ɗa’a, to ya ce musu Allah ya ishe shi komai, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai shi, gare shi shi kaɗai ya dogara ya miƙa al’amarinsa duka gare shi, shi ne Ubangijin Al’arshin nan mai girma.
Waɗannan ayoyi biyu na ƙarshe, lokacin da Sayyidina Abubakar ya kafa kwamitin tattara Alƙur’ani wuri ɗaya a ƙarƙashin jagorancin Zaidu ɗan Sabitu Al-Ansari (Allah ya kara masa yarda), da suka zo rubuta su sai aka rasa samun su a wurin kowa a rubuce sai a wurin Sahabin nan mai suna Abu Khuzaima Al-Ansari. [Dubi, Bukhari #4989].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur’ani babbar mu’ujiza ce ga Manzon Allah (ﷺ) tun daga lokacin saukarsa har zuwa tashin alƙiyama.

2. Kafirai sun riƙa mamakin Allah ya aiko mutum kamar sauran mutane a halittarsa.

3. Kowane manzo yana zuwa ne don yin gargaɗi ga masu aikata laifuka da albishir ga muminai.

4. Annabi Muhammadu (ﷺ) Manzon Allah ne zuwa ga dukkan mutane na duniya, ba Larabawa kaɗai ba.

5. Faɗar kafirai cewa Alƙur’ani sihiri ne ta nuna cewa shi wani babban abu ne da ya fi ƙarfinsu har ya gagare su kwaikwayo.



10-Suratu Yunus

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna '**Suratu Yunus**', kamar yadda yake rubuce cikin *Masahifu* da litattafan Tafsiri, da kuma haka ne aka samu sahabbai da tabi'ai suna kiran ta.

An ambace ta ne da wannan suna saboda ambaton sunan Annabi Yunus da ya zo a cikinta a aya ta (98). Ita ce kuma Surar da ta ba da labarin yadda Allah ya aiko wa mutanen Annabi Yunus (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) azaba yayin da suka ƙi yin imani da shi, to amma sai suka tuba sai ya yaye musu ita. Babu wata al'umma da aka yi wa haka sai su kaɗai.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
A wajen yawancin malamai, wasu ma sun ce ijma'i ne, Surar an saukar da ita ne a Makka, to amma Al-Hafizus Suyuɗi ya ambaci cewa, Ibnu Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, wannan Sura ce *Madaniyya*. Sai dai magana mafi inganci daga Ibnu Abbas ita ce, wannan Sura ce *Makkiyya.*

Akwai kuma wasu malamai da suka ce Sura ce *Makkiyya* amma ban da wasu ayoyi kaɗan a cikinta, su na Madina ne.
Ingantacciyar magana dai wannan Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta hamsin da ɗaya (51) a jerin saukar surori, ta sauka bayan *Suratu Isra'i*, gabanin *Suratu Hud*.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta ɗari da tara ne (109) a lissafin mafi yawan malamai, kamar kuma yadda yake rubuce a cikin *Mus'hafi*. Amma a lissafin mutanen Sham ayoyinta ɗari da goma ne (110).

5. Babban Jigonta:
Tabbatar da shikashikan Aƙidar Musulunci, kamar Tauhidi da manzanci da rayuwa bayan mutuwa.

6. Daga Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tabbatar da gaskiyar annabcin Annabi (ﷺ).
• Tabbatar da cancantar Allah Ta'ala da bauta shi kaɗai, domin shi ne mai gudanar da komai, shi ya halicci duk abin da ido ke gani da wanda ma ba ya gani.
• Hakanan a cikinta akwai dalilai masu tabbatar da girman Ƙudurar Allah da hikmomin Ubangiji.
• Surar ta yi bayani a kan masu kauce wa ayoyin Allah da ƙaryata su, da kuma bayanin azaba da narko da Allah ya yi wa al 'ummun da suka gabata.
• Ta yi bayanin misalin duniya a wajen mai imani da cewa duk wata ƙawa da ƙyale-ƙyalen duniya masu saurin gushewa ne. Saboda haka Surar tana ƙunshe da saƙonni irin na surorin Makka.

Suratu Yunus (1-2)

الٓرۚ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡحَكِيمِ ١ أَكَانَ لِلنَّاسِ عَجَبًا أَنۡ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ رَجُلٖ مِّنۡهُمۡ أَنۡ أَنذِرِ ٱلنَّاسَ وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنَّ لَهُمۡ قَدَمَ صِدۡقٍ عِندَ رَبِّهِمۡۗ قَالَ ٱلۡكَٰفِرُونَ إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٞ مُّبِينٌ ٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. *ALIF LAM RA*.
Waɗannan ayoyin littafi ne (wato Alƙur'ani) mai hikima.

2. Shin ya zama abin mamaki ga mutane cewar Mun yi wahayi zuwa ga wani mutum daga cikinsu, cewa: "Ka gargaɗi mutane, kuma ka yi wa waɗanda suka yi imani albishir cewa suna da babban matsayi wurin Ubangijinsu? Sai kafirai suka ce: "Lalle wannan tabbas mai sihiri ne mai bayyana (sihirinsa)."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da wasu haruffa domin bayanin mu'ujizar Alƙur'ani. Da waɗannan haruffa ne Larabawa suke rubutu suna karatu, to amma sun kasa kawo kamarsa. Haka kuma waɗannan ayoyi masu girman daraja ayoyi ne na Alƙur'ani mai cike da hikima.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, shin yanzu wannan ya zama abin mamaki ga kafiran Ƙuraishawa da sauran Larabawa don Allah ya yi wahayi ga wani mutum daga cikinsu, don ya zama mai gargaɗi ga dukkan mutane game da uƙubar kafirci da saɓa wa Allah, kuma ya yi wa muminai albishiri da cewa suna da wani cikakken lada wanda shi ne Aljanna, saboda kyawawan ayyukan da suka aikata? To amma sai kafirai suka riƙa mamakin wannan Manzo, har suka ce lalle shi wani matsafi ne mabayyani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah shi kaɗai ne ya cancanci a bauta masa domin shi ne ya halicci sammai da ƙasa da duk abin da yake cikinsu. Shi ne kaɗai mai ni'imtawa ga bayinsa.

2. Da Allah ya ga dama da ya halicci sammai da ƙasa a cikin ƙiftawar ido, to amma sai ya yi halittarsu a cikin kwana shida saboda wata babbar hikima da shi ya bar wa kansa sanin haƙiƙaninta. Wasu malamai sun ce yana yiwuwa hikimar yin hakan ita ce don ya nuna muhimmancin bin abubuwa a sannu ba da gaggawa ba, ko kuma don mala'iku su ga wannan halitta daki-daki su karanci ayoyi da izinonin da ke cikinsu ko kuma don wata hikimar da ya bar wa kansa saninta.

3. Allah ya ɗaukaka a kan Al'arshinsa ɗaukakar da ta dace da shi, ba ya gauraya da halittarsa.

4. Allah shi ne mai tsara dukkan al'amura, watau shi ne mai ba da izinin yadda mala'ikunsa waɗanda ya naɗa ga kowane aiki su zartar da shi kamar yadda yake so.

5. Ceto a ranar alƙiyama gaskiya ne, to amma ba zai yiwu ba sai da izinin Allah da yardarsa ga wanda za a ceta.

6. Mayar da martani ga kafirai masu musanta tashin matattu bayan mutuwa. Allah mai ikon ya fara halittarsu bayan babu su, shi ne mai ikon ya sake dawo da su masu rai bayan mutuwarsu, yin hakan ma shi ya fi sauƙi a ƙiyasin 'yan'adam.

7. Allah ya kira sakamakon da zai yi wa muminai a lahira sakamako ne na adalci, don ya saka musu nutsuwa da cewa zai ba su abin da ya yi musu alƙawarinsa bisa kyawawan ayyukansu ba tare da ya rage musu komai ba, sai dai ma ya ƙara musu daga falalarsa.

8. Kamar yadda Allah ya ambaci hujjar dake tabbatar da yiwuwar tashi bayan mutuwa, to hakanan kuma ya ambaci hikimar tashin alƙiyama,watau ita ce sakayya da adalci, kowanne mutum gwargwadon aikinsa, domin ba zai zamo adalci ko hikima ko rahama ba a daidaita sakamakon muminai da na kafirai ko na mutanen kirki da na banza ko na masu tsoron Allah da na fajirai.

9. Azabar kafirai a Jahannama iri-iri ce, daga ciki akwai azabar shayar da su tafasasshen ruwa yayin da suka nemi a ba su ruwan sha.

Suratu Yunus (3-4)

إِنَّ رَبَّكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ ۖ يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ ۖ مَا مِن شَفِيعٍ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ إِذْنِهِۦ ۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ فَٱعْبُدُوهُ ۚ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ۝٣ إِلَيْهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعًا ۖ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقًّا ۚ إِنَّهُۥ يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ لِيَجْزِىَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ بِٱلْقِسْطِ ۚ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَهُمْ شَرَابٌ مِّنْ حَمِيمٍ وَعَذَابٌ أَلِيمٌۢ بِمَا كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ ۝٤

3. Lalle Ubangijinku Shi ne Allah wanda Ya halicci sammai da ƙasa cikin kwana shida, sannan Ya daidaita a kan Al'arshi; Yana tsara al'amari (yadda Ya ga dama). Babu wani mai ceto sai da izininsa. Wannan Shi ne Allah Ubangijinku. To sai ku bauta masa. Ashe ba za ku waʾazantu ba?

4. Zuwa gare Shi ne makomarku take gaba ɗaya; alƙawarin Allah ne da gaske. Lalle Shi ne Yake farar da halitta sannan Ya maido da ita (bayan mutuwa) don Ya saka wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari da adalci. Waɗanda suka kafirce kuwa suna da abin sha mai tsananin ƙuna da kuma azaba mai raɗaɗi saboda kafircewa da suke yi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, shi ne Ubangijin talikai duka shi ne kuma wanda ya halicci sammai da ƙasa cikin kwana shida, sannan ya ɗaukaka a kan Al'arshinsa, yana tsara al'amuran halittarsa gaba ɗaya, ba kuma wanda zai yi ceto a gabansa sai da izininsa. To wannan shi ne Allah Ubangijin mutane, don haka sai su bauta masa shi kaɗai, kuma me ya sa ba za su waʾazantu ba?

Sai kuma ya bayyana cewa, makomar kowa da komai gare shi take shi kaɗai ranar da zai fitar da mutane daga ƙaburburansu rayayyu; kuma alƙawarin Allah gaskiya ne, ba ya saɓa shi, shi ne maƙagin halitta kuma ya sake mayar da ita bayan mutuwa a ranar lahira, don ya saka wa muminai da suka yi kyawawan ayyuka da adalci. Su kuwa waɗanda suka kafirta suna da sakamakon wani abin sha mai tsananin ƙuna, saboda kafircinsu a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga tuntuntuni cikin halittun Allah manya-manya na sama da na ƙasa don samun abin waʾazantuwa da ɗaukar izina da ƙaruwar imani da tsoron Allah a zuciya.

2. Bayanin falalar ilimi da bincike cikin sammai da ƙasa don ɗan'adam ya ƙara gane girman Ƙudurar Allah ya sallama masa cikin umarninsa da haninsa kamar yadda ya sallama masa kaɗaitakarsa wajen halittar waɗannan halittu da yake gani kullum.

3. Bayanin asalin ilimi na sanin lissafin lokuta da kwanakin wata da manziloli na tafiyar wata a cikin falakinsa, watau asalin ilimin falaki.

4. Ita ma rana tana tafiya ne a cikin manziloli (masaukai) kamar wata, to amma a nan an kɓance wata da ambaton tafiyarsa a cikin manziloli saboda kowa na iya ganin haka, ta hanyar ganin ƙaruwar haskensa da raguwarsa a kowace manzila, saɓanin rana da ba kowa yake gane hakan tare da ita ba.

5. Allah ya banbance siffar hasken rana da na wata, na farko ya kira shi na wata kuwa ya kira shi , domin ishara zuwa ga cewa, shi hasken rana mai zafi ne, amma hasken wata ba ya da zafi.

Suratu Yunus (5-6)

هُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ ٱلشَّمۡسَ ضِيَآءً وَٱلۡقَمَرَ نُورٗا وَقَدَّرَهُۥ مَنَازِلَ لِتَعۡلَمُواْ عَدَدَ ٱلسِّنِينَ وَٱلۡحِسَابَۚ مَا خَلَقَ ٱللَّهُ ذَٰلِكَ إِلَّا بِٱلۡحَقِّۚ يُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ۝٥ إِنَّ فِي ٱخۡتِلَٰفِ ٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَتَّقُونَ ۝٦

5. Shi ne Wanda Ya sanya muku rana ta zamo mai haske da kuma wata ya zamo mai haskakawa, Ya kuma sanya shi mai masaukai don ku san adadin shekaru da kuma (sanin) lissafi (na lokuta). Allah bai halicci wannan ba sai da gaskiya. Yana bayyana ayoyi ne ga mutanen da suke da sani.

6. Lalle game da sassaɓawar dare da rana da kuma abubuwan da Allah Ya halitta cikin sammai da ƙasa akwai ayoyi ga mutanen da suke kiyaye dokokin Allah.

A waɗannan ayoyi bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da Rububiyyarsa da Uluhiyyarsa, sai kuma ya bayyana wasu dalilai da duk masu hankali suke gani kullum waɗanda kuma suke tabbatar da Rububiyyarsa da Uluhiyyarsa. Ya bayyana cewa, shi ne Allah wanda ya sanya rana mai haske da rana, ya kuma mayar da wata mai haskakawa da daddare, ya kuma ƙaddara tafiyar wannan watan a cikin manziloli (masaukai) don mutane su san adadin yawan shekaru, kuma su san lissafin yawan darare da watanni. Allah bai halicci wannan ba sai bisa gaskiya, yana kuma bayyana wa mutane masu ganewa hujjoji da dalilai.
Allah kuma ya ci gaba da bayanin cewa, shi kuma sassaɓawar dare da yini, watau wannan ya zo wannan ya tafi wannan ya tafi wannan ya zo, hakanan da abin da ya halitta a cikin sammai da ƙasa, tabbas waɗannan duka dalilai ne ƙarara masu nuna samuwar Allah mahalicci wanda shi kaɗai ne ya cancanci a bauta masa, kuma zuwa gare shi makoma take a ranar gobe ƙiyama, amma ga mutane masu taƙawa suna kiyaye dokokin Allah Ta'ala.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gwargwadon yadda mutum ya bijire wa shiri game da lahirarsa, hakanan yake kutsawa cikin son duniya da rungumar ta hannu bibbiyu ba tare da tunani ba.

2. Aljanna ta ƙunshi dangogin ni'imomi daban-daban, kama daga ni'imar nutsuwar zuciya da kwanciyar hankali da farin ciki har zuwa ga mafi girman ni'ima a Aljanna, ita ce ni'imar ganin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Shi ne ya sa Allah ya jingina ambaton gidan Aljanna zuwa ga ni'ima domin cikarta da kammaluwarta a wannan gida.

3. *Tasbihi*, watau faɗar: ‘Subhanallahi’’ da *Tahmidi*, watau faɗar: ‘‘*Alhamdulillahi*’’ hakanan da *Tahlili*, watau faɗar: "La *ilaha illallahu’’*, duk waɗannan ana iya kiran su addu’a.

4. Allah shi ne abin yabo a wurin muminai a koyaushe, har a cikin Aljanna bayan ya saka su cikinta.

5. Falala da girman martabar sallama, domin za ta kasance ita ce gaisuwar ‘yan Aljanna a lahira.

Suratu Yunus (7-10)

إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا وَرَضُواْ بِٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَٱطۡمَأَنُّواْ بِهَا وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَنۡ ءَايَٰتِنَا غَٰفِلُونَ ٧ أُوْلَٰٓئِكَ مَأۡوَىٰهُمُ ٱلنَّارُ بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٨ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ يَهۡدِيهِمۡ رَبُّهُم بِإِيمَٰنِهِمۡۖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمُ ٱلۡأَنۡهَٰرُ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ٩ دَعۡوَىٰهُمۡ فِيهَا سُبۡحَٰنَكَ ٱللَّهُمَّ وَتَحِيَّتُهُمۡ فِيهَا سَلَٰمٞۚ وَءَاخِرُ دَعۡوَىٰهُمۡ أَنِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٠

7. Lalle waɗanda ba sa tsammanin gamuwa da Mu, suka kuma yarda da rayuwar duniya, kuma suka nutsu da ita, da kuma waɗanda suke gafala daga ayoyinmu.

8. Waɗanan makomarsu wuta ce saboda abin da suka kasance suna aikatawa.

9. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, Ubangijinsu zai shirye su saboda imaninsu: ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu cikin aljannatai na ni’ima.

10. Addu’arsu a cikinta: ‘‘Muna tsarkake Ka ya Allah’’, gaisuwarsu kuma a cikinta ‘‘Salamun’’ (watau aminci). Ƙarshen addu’arsu kuma ita ce: ‘‘Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai.’’

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin waɗanda suka kafirce wa Allah Ta’ala duk kuwa da bayyanar dalilai ƙarara gare su. Ya bayyana cewa, waɗanda ba sa tsammanin gamuwa da Allah a ranar alƙiyama, suka kuma yarda da rayuwar duniya maimakon ta lahira, suka nutsu da ita da kuma waɗanda suka bijire wa ayoyin Allah, to waɗannan makomarsu da mazauninsu ita ce wutar Jahannama a ranar lahira, saboda abin da suka kasance suna aikatawa na kafirci da saɓon Allah.
Sannan kuma ya bayyana cewa, tabbas waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, Ubangijinsu zai shiryar da su a lahira ga gidajen Aljanna saboda imaninsu; ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu cikin gidajen Aljanna na ni’ima. Addu’arsu a cikin Aljanna ita ce, za su riƙa cewa: ‘‘Tsarki ya tabbata gare ka ya Allah.’’ Gaisuwarsu ga junansu kuwa ita ce: ‘‘Salamun’’, watau aminci ya tabbata a gare ku. Ƙarshen addu’arsu kuwa ita ce: ‘‘Godiya da yabo sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai.’’

An karɓo daga Jabiru ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: ‘‘Lalle ‘yan Aljanna suna ci suna kuma sha a cikinta, amma ba sa tofar da yawu ba kuma sa yin fitsari, kuma ba sa bahaya, ba kuma sa yin kaki.’’ Sai sahabbai suka ce: ‘‘To ta ƙaƙa za su fitar da abinci?’’ Sai ya ce: ‘‘Ta hanyar gyatsa da gumi mai ƙanshin turaren almiski, za a kimsa musu yin tasbihi da godiya ga Allah kamar yadda suke yin numfashi.’’ [Muslim #2835].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin wata mummunar ɗabi’a ta ɗan’adam, watau ƙarancin haƙuri yayin da wata musiba ta auka masa, sannan kuma mai ƙarancin godiya ga Allah yayin da ya yi masa wata ni’ima ko ya yaye masa wata cuta.

2. Tausayin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa yana da yawa, alherinsa gare su kuma mai kwarara ne ko da yaushe yana kare su daga sharrin abin da suke jawo wa kansu da kansu.

3. Ɗan'adam mai yawan addu'a ne yayin da yake cikin wahala, amma mai saurin mantawa ne da Ubangijinsa yayin da yake cikin ni'ima. Ya wajaba mutum ya kasance mai yawan roƙon Allah ne tare da gode masa lokacin da yake cikin ni'ima don Allah ya karɓi addu'arsa lokacin da ya tsinci kansa a cikin tsanani.

Suratu Yunus (11-12)

*وَلَوۡ يُعَجِّلُ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ ٱلشَّرَّ ٱسۡتِعۡجَالَهُم بِٱلۡخَيۡرِ لَقُضِيَ إِلَيۡهِمۡ أَجَلُهُمۡۖ فَنَذَرُ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ١١ وَإِذَا مَسَّ ٱلۡإِنسَٰنَ ٱلضُّرُّ دَعَانَا لِجَنۢبِهِۦٓ أَوۡ قَاعِدًا أَوۡ قَآئِمٗا فَلَمَّا كَشَفۡنَا عَنۡهُ ضُرَّهُۥ مَرَّ كَأَن لَّمۡ يَدۡعُنَآ إِلَىٰ ضُرّٖ مَّسَّهُۥۚ كَذَٰلِكَ زُيِّنَ لِلۡمُسۡرِفِينَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٢

11. Da dai Allah zai gaggauta (karɓar addu'ar) mutane ta sharri kamar yadda yake gaggauta ta alheri to da ƙarshen rayuwarsu ya zo. Sai dai Mukan bar waɗanda ba sa tsammanin haɗuwa da Mu cikin shisshigin su yi ta faganniya.

12. Idan kuma wata cuta ta sami mutum, sai ya roƙe Mu, a kishingiɗe ne ko a zaune ko kuwa a tsaye. To lokacin da Muka yaye masa cutarsa sai ya ci gaba (da halinsa) kamar bai taɓa roƙon Mu game da wata cuta da ta shafe shi ba. Kamar haka ne aka ƙawata wa maɓarnata abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, da zai gaggauta karɓar addu'ar mutane ta sharri kamar yadda yake gaggauta karɓar ta alhairi, to da sun halaka gaba ɗaya. Allah kuma zai bar waɗanda ba sa sa ran haɗuwarsu da shi a lahira cikin ɗimuwa da fagamniya cikin ɓatansu.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kada ku yi wa kawunanku mummunar addu'a, kada kuma ku yi ga 'ya'yanku ko dukiyoyinku, don kada ku dace da wani lokaci da ake roƙon Allah a cikinsa sai ya amsa muku addu'arku." [Muslim #3009].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cewa, idan wata cuta ta sami mutum sai ya roƙi Allah don ya yaye masa, a tsaye yake ko a zaune ko a kishingiɗe, watau a cikin kowane hali ya samu kansa yakan yi addu'a, to amma idan Allah ya yaye masa cutarsa sai ya ci gaba da kafircinsa da saɓon Allah, ya manta halin da ya shiga a baya na tsanani, ba kuma zai gode wa Allah da ya yaye masa cutarsa ba, ya nuna kamar ma bai taɓa roƙon Allah ba game da wata cuta da ta same shi. Allah ya bayyana cewa kamar haka ne aka ƙawata wa kafirai masu azarɓaɓi cikin kafircinsu da saɓon Allah abin da suka kasance suna aikatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zalunci yana ɗaya daga cikin abubuwan da suka jawo hallakar al 'ummun da suka gabata.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da wannan al'umma ne a madadin al 'ummun da suka gabata, ya ba su ni'imomi da yawa na duniya don ya jarraba su ya ga su kuma me za su aikata.

3. Jawo hankalin wannan al'umma domin su ɗauki wa'azi daga waɗanda suka gabace su.

Suratu Yunus (13-14)

وَلَقَدۡ أَهۡلَكۡنَا ٱلۡقُرُونَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَمَّا ظَلَمُواْ وَجَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَمَا كَانُواْ لِيُؤۡمِنُواْۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡمُجۡرِمِينَ١٣ ثُمَّ جَعَلۡنَٰكُمۡ خَلَٰٓئِفَ فِي ٱلۡأَرۡضِ مِنۢ بَعۡدِهِمۡ لِنَنظُرَ كَيۡفَ تَعۡمَلُونَ١٤

13. Haƙiƙa kuma Mun hallaka al 'ummun da suka gabace ku, lokacin da suka yi zalunci, kuma manzanninsu suka zo musu da (hujjoji) mabayyana, sai ba su zamana sun yi imani ba. Kamar haka ne Muke saka wa mutane masu laifi.

14. Sannan bayansu Muka mayar da ku madadinsu a bayan ƙasa don Mu ga me za ku aikata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa mushirikai kashedi da cewa, shi ne fa ya hallaka al 'ummun da suka gabace su lokacin da suka yi zalunci ta hanyar shirka da Allah da ƙaryata annabawa da zaluntar masu rauni. Manzannin Allah sun kawo wa waɗannan al 'ummu mu'ujizoji bayyanannu, to amma sai suka ƙi su yi imani domin Allah ya toshe musu zukatansu saboda kafircinsu da tsaurin kansu ga gaskiya, to kamar haka ne Allah yake saka wa mutane masu manyan laifuka. Sannan bayan hallakar da waɗancan, sai ya mayar da waɗannan suka maye gurbinsu don ya ga me su kuma za su aikata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafiran Makka sun nemi ɗayan abubuwa biyu daga Annabi (ﷺ), a kan cewa idan ya yi ɗaya daga cikinsu to za su ba da gaskiya da shi. Abubuwan su ne:
Ko dai ya kawo musu wani sabon alƙur'anin wanda ba ya ɗauke da sukan wani abu na addininsu ko halayensu. Ko kuma ya canza Alƙur'anin, watau ya cire duk wata aya da aka soke su aka soki gumakansu a dawo da yabo gare su, hakanan duk inda aka yabi abin da ba sa so ya mayar da shi suka. Annabi (ﷺ) ya nuna musu cewa, ko canza ayoyin ma ba zai iya yi ba ballantana ya zo da wani sabon lƙur'anin ɗungurungum.

2. Allah ne kaɗai yake da ikon ya musanya wata aya a Alƙur'ani da wata, kamar yadda ya nuna a cikin Suratun Nahli, aya ta 101 ko Suratul Baƙara, aya ta 106.

3. Zuwan Alƙur'ani ta hannun wanda bai iya karatu da rubutu ba, bai kuma taɓa karanta wani littafi ba, bai taɓa neman ilimi a wurin kowa ba, wannan babban dalili ne a kan cewa Alƙur'anin daga Allah yake.

4. Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) yana bin wahayi ne, bai taɓa ƙirƙiro wani abu na addini da kansa ba ya ce a zo a bi.

Suratu Yunus (15-17)

وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَاتُنَا بَيِّنَٰتٖ قَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا ٱئۡتِ بِقُرۡءَانٍ غَيۡرِ هَٰذَآ أَوۡ بَدِّلۡهُۚ قُلۡ مَا يَكُونُ لِيٓ أَنۡ أُبَدِّلَهُۥ مِن تِلۡقَآيِ نَفۡسِيٓۖ إِنۡ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّۖ إِنِّيٓ أَخَافُ إِنۡ عَصَيۡتُ رَبِّي عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ١٥ قُل لَّوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَا تَلَوۡتُهُۥ عَلَيۡكُمۡ وَلَآ أَدۡرَىٰكُم بِهِۦۖ فَقَدۡ لَبِثۡتُ فِيكُمۡ عُمُرٗا مِّن قَبۡلِهِۦٓۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ١٦ فَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوۡ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ١٧

15. Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu bayyanannu sai waɗanda ba sa tsammanin haɗuwa da mu su ce: “Ka zo da wani alƙur’anin ba wannan ba, ko kuma ka canja shi.” Ka ce (da su): “Bai dace da ni ba in canja shi da raɗin kaina. Ni ba abin da nake bi sai abin da kawai aka yo mini wahayi. Lalle ni dai ina tsoron azabar rana mai girma idan na saɓa wa Ubangijina.”

16. Ka ce: “Da Allah Ya ga dama da ban karanta muku shi ba, kuma da (Allah) bai sanar da ku shi ba, domin haƙiƙa na zauna cikinku shekaru masu yawa tun gabaninsa. Me ya sa ba za ku hankalta ba?”

17. To ba wanda ya fi zalunci irin wanda ya ƙirƙira wa Allah ƙarya ko kuma ya ƙaryata ayoyinsa. Lalle masu babban laifi ba za su rabauta ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, idan ana karanta wa mushirikai ayoyin Alƙur’ani sai waɗanda ba sa tsammanin haɗuwa da Allah, masu ƙaryata ranar alƙiyama su ce wa Manzon Allah (ﷺ) ya zo da wani alƙur’anin wanda a cikinsa babu abin da ba sa so, ko kuma ya canja shi shi da kansa yadda yake so. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya ba su amsa da cewa, al’amarin canja Alƙur’ani da wani ko canja wasu ayoyinsa ba a hannunsa yake ba, shi ma ba abin da yake bi sai abin da kawai aka yi masa wahayinsa, kuma shi haƙiƙa yana jin tsoron azabar rana mai girma, watau alƙiyama, idan har ya saɓa wa Ubangijinsa.
Allah kuma ya umarce shi, har ila yau, ya faɗa musu cewa, da Allah ya ga dama da Annabi bai karanta musu Alƙur’ani ba, kuma da Allah bai sanar da su shi ba. Haƙiƙa kuma ya zauna a cikinsu -su mutanen Makka- shekaru masu yawa, kimanin arba’in, tun kafin a yi masa wahayin Alƙur’ani, amma ba su taɓa kama shi da laifin ƙarya ba; sun san shi mai gaskiya ne mai amana; to me ya sa ba za su hankalta ba su fahimci cewa Alƙur’ani wahayi ne daga Allah?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu wanda ya fi zalunci irin wanda ya ƙirƙira wa Allah ƙarya, ko kuma ya ƙaryata ayoyinsa. Lalle kuwa masu manyan laifuka irin waɗannan ba sa rabauta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Harsashin ginin aƙidar shirka da Allah shi ne: Duk masu bauta a kan tafarkin shirka da Allah suna ganin ba su cancanci su fuskanci Allah kai-tsaye da wata buƙatarsu ba; dole ne wai sai sun yi kamun ƙafa da wasu alloli wai saboda su ba tsarkaka ne ba, don haka suna buƙatar kamun ƙafa da tsarkakan abubuwa zuwa ga Allah. Saɓanin addinin da aka gina a kan Tauhidi mai yake karantar da ‘ya’yansa cewa kowa yana iya kusantar Ubangijinsa, ko da kuwa yana tattare da ƙazantar saɓon Allah, ana buƙatar sa da ya fuskanci Ubangijinsa ta hanyar tuba, don ya yafe masa laifukansa.

2. Bayanin cewa mushirikai sun yarda da cewa ababen bautarsu waɗanda ba Allah ba, ba su yi tarayya da Allah wajen halittar sammai da ƙasa ba; suna dai bauta musu ne kawai don wai su cece su a wajen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Bayani a kan cewa wanda ya cancanci a bauta masa shi ne kawai wanda yake da ikon cutarwa ko amfanarwa.

4. Asalin addinin da mutane suke a kai shi ne Tauhidi, daga baya ne suka kafirce.

5. Gaskiya guda ɗaya ce.

6. Tsoratarwa da gargaɗi a kan saɓanin addinin da zai kai ga ƙetare iyaka da rarrabuwar kai.

7. Allah ne kaɗai ya san gaibi, babu wanda ya san shi sai abin da Allah ya ga dama ya yi masa wahayin sa ga wani annabi ya sanar da shi, to daga nan kuwa ya fita daga matsayin gaibi da ake magana a kansa.

Suratu Yunus (18-20)

وَيَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَضُرُّهُمۡ وَلَا يَنفَعُهُمۡ وَيَقُولُونَ هَٰٓؤُلَآءِ شُفَعَٰٓؤُنَا عِندَ ٱللَّهِۚ قُلۡ أَتُنَبِّـُٔونَ ٱللَّهَ بِمَا لَا يَعۡلَمُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ١٨ وَمَا كَانَ ٱلنَّاسُ إِلَّآ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ فَٱخۡتَلَفُواْۚ وَلَوۡلَا كَلِمَةٞ سَبَقَتۡ مِن رَّبِّكَ لَقُضِيَ بَيۡنَهُمۡ فِيمَا فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ١٩ وَيَقُولُونَ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ ءَايَةٞ مِّن رَّبِّهِۦۖ فَقُلۡ إِنَّمَا ٱلۡغَيۡبُ لِلَّهِ فَٱنتَظِرُوٓاْ إِنِّي مَعَكُم مِّنَ ٱلۡمُنتَظِرِينَ ٢٠

18. Suna kuma bauta wa wani ba Allah ba, abin da ba zai cutar da su ba ba kuma zai amfane su ba, suna kuma cewa: “Waɗannan su ne masu ceton mu a wurin Allah.” Ka ce: “Shin yanzu za ku ba Allah labarin abin da bai sani ba ne a cikin sammai ko kuma a bayan ƙasa? Tsarki ya tabbata a gare Shi Ya kuma ɗaukaka daga abin da suke shirka da Shi.”

19. A da can mutane sun zamanto al’umma ɗaya ce, to sai suka sassaɓa. Da ba don wata kalma da ta gabata daga Ubangijinka ba, to da an yi hukunci a tsakaninsu game da abin da suke sassaɓawa a kai.

20. Suna kuma cewa: “Don me ba a saukar masa da wata aya daga Ubangijinsa ba?” To ka ce: “Sanin gaibu na Allah ne kawai, sai ku saurara, lalle ni ma ina tare da ku cikin masu sauraro.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin cewa, mushirikai suna bauta wa wanin Allah wanda ba zai iya cutar da su ba kuma ba zai amfane su da komai ba, suna cewa, wai suna bauta wa gumakan ne don za su cece su a wurin Allah, to amma Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Muhammadu (ﷺ) da ya faɗa musu cewa, shin yanzu su za su ba wa Allah labarin abin da bai sani ba ne a cikin sammai ko a ƙasa? Allah ya tsarkaka daga duk wata shirka da suke yi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a da mutane gaba ɗaya suna bin addini ɗaya ne na kaɗaita Allah, sai suka sassaɓa a addininsu, suka fara haɗa Allah da wasu wajen bauta. Ba don Allah ya riga ya yanke hukuncin cewa zai saurara wa mushirikai da masu saɓon Allah ba, watau zai jinkirta yi musu sakamako zuwa ranar alƙiyama, to da tabbas ya yi hukunci a kan waɗanda suka sassaɓa tun a nan duniya, ya tserar da muminai ya kuma gaggauto azabarsa ga kafirai.
Sannan Allah ya bayyana cewa, su waɗannan mushirikai suna cewa me ya hana a saukar wa da Annabi (ﷺ) irin mu’ujizojin da suke neman a saukar masa domin su tabbatar da cewa shi da gaske Manzo ne daga Allah? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa musu cewa, ai saukar da waɗannan mu’ujizoji yana daga cikin lamura na gaibu wanda babu wanda ya san shi sai Allah, kuma babu mai iya saukar da su sai shi idan ya ga dama, idan kuma ya ga dama ya ƙi saukarwa, don haka Allah ya umarce shi ya faɗa musu cewa, su saurara su ga irin uƙubar da Allah zai yi wa masu ƙarya daga cikinsu da kuma nasarar da zai ba masu gaskiya, Annabi da sahabbansa ma suna tare da su suna sauraro.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin mummunan halin ɗan’adam na butulci; idan Allah ya ni’imta shi da ni’imominsa, to maimakon ya karɓe su da godiya ga wanda ya ba shi, watau Allah, sai ya shiga ƙulle-ƙullen makircin faɗa da addinin Allah ko karya gaskiya da dasa ɓarna.

2. Mushirikai na farkon wannan al'umma sun kasance suna aikata shirkarsu ne lokacin da suke cikin ni'ima da walwala, amma idan sun shiga halin tsanani da bala'i sai su koma ga Allah shi kaɗai, saɓanin halin wasu a cikin Musulmi a yau, sukan kasance cikin shirka da Allah yayin da suke cikin walwala ko tsanani.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana amsa addu'ar wanda yake cikin matsuwa ko da kuwa shi kafiri ne.

4. Halaccin tafiye-tafiye a cikin jiragen ruwa.

Suratu Yunus (21-23)

وَإِذَآ أَذَقْنَا ٱلنَّاسَ رَحْمَةً مِّنۢ بَعْدِ ضَرَّآءَ مَسَّتْهُمْ إِذَا لَهُم مَّكْرٌ فِىٓ ءَايَاتِنَا ۚ قُلِ ٱللَّهُ أَسْرَعُ مَكْرًا ۚ إِنَّ رُسُلَنَا يَكْتُبُونَ مَا تَمْكُرُونَ ﴿٢١﴾ هُوَ ٱلَّذِى يُسَيِّرُكُمْ فِى ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا كُنتُمْ فِى ٱلْفُلْكِ وَجَرَيْنَ بِهِم بِرِيحٍ طَيِّبَةٍ وَفَرِحُوا۟ بِهَا جَآءَتْهَا رِيحٌ عَاصِفٌ وَجَآءَهُمُ ٱلْمَوْجُ مِن كُلِّ مَكَانٍ وَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُمْ أُحِيطَ بِهِمْ دَعَوُا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ لَئِنْ أَنجَيْتَنَا مِنْ هَٰذِهِۦ لَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿٢٢﴾ فَلَمَّآ أَنجَىٰهُمْ إِذَا هُمْ يَبْغُونَ فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ ۗ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّمَا بَغْيُكُمْ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُم ۖ مَّتَٰعَ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ ثُمَّ إِلَيْنَا مَرْجِعُكُمْ فَنُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٢٣﴾

21. Idan kuma Muka ɗanɗana wa mutane dadî bayan wahala ta same su, sai ga su suna ƙulla makirci ga ayoyinmu. Ka ce: "Allah Ya fi gaggawar (sakayya a kan) makirci." Lalle manzanninmu suna rubuta abin da kuke ƙullawa na makirci.

22. Shi ne Wanda Yake tafiyar da ku a tudu da cikin ruwa, har lokacin da kuka shiga cikin jiragen ruwa, (jiragen) kuwa suka yi gudu da su tare da iska mai dadî, suka kuma yi farin ciki da su (jiragen) sai kuma wata iska mai ƙarfi ta zo musu; raƙumin ruwa kuma ya zo musu ta kowane wuri, suka kuma tabbatar cewa dai su kam an rutsa da su, sai kuma suka roƙi Allah suna masu tsarkake addini gare Shi (suna cewa): "Tabbas idan Ka tserar da mu daga wannan, lalle haƙiƙa za mu zamo cikin masu godiya."

23. To lokacin da Ya tserar da su sai ga su suna ɓarna a bayan ƙasa ba da gaskiya ba. Ya ku mutane, haƙiƙa (sakamakon) ɓarnarku a kanku kawai yake; ku ɗan ji dadîn rayuwar duniya; sannan (daga ƙarshe) zuwa gare Mu ne makomarku take, sannan mu ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin halin mushirikai ne cewa, idan ya ɗanɗana musu wani dadî bayan wahala da musiba da ta same su, sai ka gan su suna ta ƙoƙarin ƙulle-ƙullen makircin yadda za su rusa gaskiya su kafa ƙarya; to Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabinsa (ﷺ) ya faɗa musu cewa, Allah ya fi su gaggawar zartar da kowane irin makirci, manzanninsa kuma daga cikin mala'iku suna nan suna rubuta duk wani makirci da kafirai suke ƙullawa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi ne wanda yake tafiya da su a kan tudu da kuma cikin ruwa, har lokacin da suka kasance cikin jiragen ruwa, waɗanda suke yin gudu da su tare da iska mai dadî, mahaya jiragen kuma suka yi murna da su, sai kuma ga wata iska mai ƙarfi ta taso musu, raƙumin ruwa ya zo musu ta kowane ɓangare, a nan suka tabbatar halaka ta kewaye su ta ko'ina, sai suka shiga roƙon Allah suna masu tsantsanta addini gare shi cewa, lalle idan har ya tserar da su daga wannan halakar, to tabbas suna rantsuwa za su zama cikin masu godiya.

An karɓo daga Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "A ranar da aka buɗe garin Makka sai Annabi (ﷺ) ya amintar da kowa in ban da maza huɗu da mata biyu, ya ce: "Ku kashe su ko da kuwa kun same su ne maƙale a jikin rigar ɗakin Allah (Ka'aba)." Waɗannan mutane kuwa su ne Ikrima ɗan Abu Jahlin da Abdullahi ɗan Khaɗal da Abdullahi ɗan Sahal ɗan Abus-Sarh. To amma shi Ikrima sai ya gudu ya hau

jirgin ruwa sai guguwa mai tsanani ta taso musu, sai mutanen cikin jirgin suka ce wa junansu: “Ku tsantsanta addu’a ga Allah shi kaɗai domin kuwa a yau dai gumakanku ba za su tsinana muku komai ba.” Sai Ikrima ya ce a ransa: “Idan dai har a yau cikin wannan teku babu abin da zai kuɓutar da ni sai tsantsanta addu’a ga Allah shi kaɗai, watau ikhlasi, to har a waje ma babu abin da zai kuɓutar da ni sai ikhlasi kaɗai. Ya Allah, na yi maka alƙawari idan har ka tserar da ni daga wannan musiba da nake ciki a yanzu, to zan je wurin Muhammadu (ﷺ) in saka hannuna a cikin hannunsa, na tabbata lalle zan same shi mai yafiya ne mai karamci.” Sai ya zo wurinsa ya musulunta.” [Nasa’i #4067 da Al-Bazzar #1151].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, su waɗannan kafirai idan Allah ya tserar da su sai su saɓa masa alƙawarin da suka yi masa, kuma su yi ta ɓarna a bayan ƙasa suna haɗa Allah da wasu wajen bauta, suna saɓon Allah da zalunci ba tare da wani haƙƙi ba. Allah ya sanar da su cewa waɗannan abubuwa duk da suke yi na zalunci da shirka da saɓon Allah ana ƙyale su, musibar daga ƙarshe kansu za ta dawo, kuma duk wannan abu na cuta da suke yi za su ji ɗan dadinsa ne kaɗan na duniya ba mai ɗorewa ba, sannan makomarsa gaba ɗaya zuwa ga Allah ne ranar alƙiyama, ya ba su labarin abin da suka aikata a duniya mai kyau da marar kyau, sannan ya yi musu sakayya a kansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya buga misalin rayuwar duniya da ruwan sama ba da ruwan ƙasa ba, domin ruwan sama mutum ba shi da wani iko a kansa ta fuskar ƙaruwarsa ko raguwarsa, saɓanin ruwan ƙasa, wanda ɗan’adam yana da wani kataɓus a kai. Don haka yin kwatance da ruwan saman ya fi dacewa.

2. Wannan duniyar da mutane suke faɗa da juna wajen tara ta, har suke mantawa da lahira gaba ɗaya don su samu wani ɗan jin dadinta ƙanƙani, aba ce da babu nutsuwa ko tabbata tare da ita, su kansu mutanen ba su da wani iko a kanta sai gwargwadon abin da Allah ya hore musu.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana kiran kowa da kowa zuwa ga hanyar shiga gidan Aljanna, to amma ba kowa ne zai amsa wannan kiran ba sai wanda Allah ya ga damar shiryar da shi zuwa ga tafarki madaidaici saboda ya nuna miƙa wuyansa ga zaɓin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Yunus (24-25)

إِنَّمَا مَثَلُ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا كَمَآءٍ أَنزَلْنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخْتَلَطَ بِهِۦ نَبَاتُ ٱلْأَرْضِ مِمَّا يَأْكُلُ ٱلنَّاسُ وَٱلْأَنْعَٰمُ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَخَذَتِ ٱلْأَرْضُ زُخْرُفَهَا وَٱزَّيَّنَتْ وَظَنَّ أَهْلُهَآ أَنَّهُمْ قَٰدِرُونَ عَلَيْهَآ أَتَىٰهَآ أَمْرُنَا لَيْلًا أَوْ نَهَارًا فَجَعَلْنَٰهَا حَصِيدًا كَأَن لَّمْ تَغْنَ بِٱلْأَمْسِ ۚ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿٢٤﴾ وَٱللَّهُ يَدْعُوٓا۟ إِلَىٰ دَارِ ٱلسَّلَٰمِ وَيَهْدِى مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٢٥﴾

24. Misalin rayuwar duniya kawai kamar ruwa ne da Muka saukar da shi daga sama, to sai shukokin da suke kan ƙasa suka cuɗanya da shi daga abin da mutane da dabbobi suke ci; har lokacin da ƙasa ta ƙawata (da shi) ta kuma yi ado; masu ita kuma suka sakankance cewa su masu ikon cin amfaninta ne, sai ƙaddararmu ta zo mata cikin dare ko rana, sai Muka mayar da ita girbabbiya kamar daɗai ba ta rayu ba a jiya. Kamar haka Muke bayyana ayoyi ga mutanen da suke tunani.

25. Allah kuwa Yana kira ne zuwa gidan aminci (wato Aljanna), Yana kuma shiryar da wanda Ya ga dama zuwa tafarki madaidaici.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, misalin ƙyale-ƙyalen duniya da saurin gushewarsa kamar ruwan sama ne da Allah ya saukar da shi a ƙasa; to sai shukoki iri-iri suka fito a

sanadiyyarsa, sashinsu ya cuɗanya da sashi daga abin da mutane da dabbobi suke ci, har lokacin da ƙasa ta yi kyau ta kuma yi ado da nauʾukan tsirrai daban-daban da furanni masu mabambantan launi, masu ita kuma suka sakankance cewa su masu ikon girbe ta ne su ci amfaninta, sai kwatsam ƙaddarar Allah ta afkar mata, Allah ya mayar da amfaninta girbabbe kuma lalatacce kamar daɗai ba a taɓa yin wata gona a wurin ba. To kamar haka ne Allah yake bayyana ayoyinsa daki-daki ga mutanen da suke tunani.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi yana kiran bayinsa su zo su shiga gidan Aljanna wanda babu wata cutarwa a cikinsa, yana kuma datar da wanda ya ga dama daga cikin bayinsa a kan bin wannan hanyar miƙaƙƙiya har zuwa ga gidan Aljanna, watau addinin Musulmi.

An karɓo daga Jabiru ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Malaʾiku sun zo wa Annabi (ﷺ) yana barci, sai wasu daga cikinsu suka ce: "Lalle yana barci ne." Sai wasu suka ce: "Lalle idon ne yake barci amma zuciyar a farke take." Sai wasu suka ce: "Mutumin nan naku yana da wani misali, ku faɗi misalinsa." Sai wasu suka ce: "Ai barci yake." Sai wasu suka ce: "Lalle idon ne yake barci amma zuciyar a farke take." Sai suka ce: "Misalinsa kamar wani mutum ne da ya gina gida, ya shirya kaɓakin abinci a cikinsa, ya kuma aika mai gayyata, to duk wanda ya amsa kiran mai gayyatar, zai shiga wannan gida ya ci abincin wannan kaɓakin, wanda kuwa bai amsa kiran mai gayyata ba, to ba zai sami shiga wannan gida ba har ya ci abincin wannan kaɓaki." Sai suka ce wa juna: "Ku fassara wannan maganar don ya fahimce ta." Sai wasu suka ce: "Barci yake yi." Sai wasu suka ce: "Idon ne mai barci amma zuciyar a farke take." Sai suka ce: "Wannan gidan shi ne Aljanna, wannan mai gayyata kuma shi ne Muhammadu (ﷺ), to duk wanda ya bi Muhammadu (ﷺ) to lalle ya bi Allah, wanda kuwa ya saɓa wa Muhammadu (ﷺ) to haƙiƙa ya saɓa wa Allah; Muhammadu kuma mai rarrabewa ne tsakanin mutane (watau tsakanin 'yan wuta da 'yan Aljanna." [Bukhari #7281].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin yalwar falalar Allah ga bawansa; yayin da bawa ya kyautata aikinsa Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa sakayya da sakamakon da ya fi aikinsa kyau.

2. Muminai a lahira za su ga Ubangijinsu mai girma da buwaya.

3. Yayin da bayin Allah na ƙwarai suka bauta masa kamar suna ganin sa, sai ya yi musu sakayya da ba su damar ganin sa a lahira.

4. Babu mai kare wani daga azabar Allah a duniya ko a lahira, masu laifuka a nan duniya sukan manta ko su ƙaryata hakan, to amma bayan mutuwa za su tabbatar da cewa babu wani mai kare su daga azabar Allah.

Suratu Yunus (26-27)

*لِّلَّذِينَ أَحۡسَنُواْ ٱلۡحُسۡنَىٰ وَزِيَادَةٞۖ وَلَا يَرۡهَقُ وُجُوهَهُمۡ قَتَرٞ وَلَا ذِلَّةٌۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٦ وَٱلَّذِينَ كَسَبُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ جَزَآءُ سَيِّئَةِۭ بِمِثۡلِهَا وَتَرۡهَقُهُمۡ ذِلَّةٞۖ مَّا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِنۡ عَاصِمٖۖ كَأَنَّمَآ أُغۡشِيَتۡ وُجُوهُهُمۡ قِطَعٗا مِّنَ ٱلَّيۡلِ مُظۡلِمًاۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٧

26. Waɗanda suka kyautata aiki suna da sakamako mafi kyau (watau Aljanna) da kuma ƙari. Wani ƙunci da ƙaskanci kuma ba za su same su ba. Waɗannan su ne 'yan Aljanna; su masu dawwama ne a cikinta.

27. Waɗanda kuma suka yi mummunan aiki, to sakamakon mummunan aiki irinsa ne, kuma ƙasƙanci zai lulluɓe su; ba su da wani mai kare su daga (azabar) Allah; kamar dai an lulluɓe fuskokinsu ne da wani yanki na dare mai duhu ƙirin. Waɗannan su ne ‘yan wuta; su kuma masu dawwama ne a cikinta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, lalle waɗanda suka kyautata ayyukansu a duniya suna da sakamakon gidan Aljanna a lahira da ma ƙari a kan hakan. Mafi girman ƙarin sakamako da Allah zai yi wa ‘yan Aljanna shi ne ya ba su damar ganin fuskarsa mai daraja kamar yadda ayoyi na 22 da 23 na cikin Suratul Ƙiyama suka nuna.

An karɓo daga Suhaibu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Idan ‘yan Aljanna suka shiga gidan Aljanna sai Allah Tabaraka wa Ta’ala ya ce: “Kuna son ƙarin wani abu in ƙara muku?” Sai su ce: “Ashe ba ka haskaka mana fuskokinmu ba? Ashe ba ka shigar da mu gidan Aljanna ba, ka kuma tserar da mu daga wuta?” Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Sai Allah ya yaye shamaki; to babu wani abu da aka ba su da ya fi soyuwa a wurinsu kamar ganin Ubangijinsu mai girma da buwaya.” Sannan ya karanta wannan ayar.” [Muslim #181].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗin sakamakon ‘yan Aljanna bayan sun shige ta, yana cewa wani ƙunci ko wulaƙanci da ƙasƙanci ba zai rufe musu fuskokinsu ba. Waɗannan su ne ‘yan Aljanna masu zama a cikinta har abada.
Sannan kuma Allah ya bayyana sakamakon waɗanda suka yi mummunan aiki a duniya suka kafirce wa Allah da Manzonsa, to su kam suna da wani mummunan sakamako, kowa gwargwadon munin aikinsa na duniya, wulaƙanci da ƙasƙanci da taɓewa za su lulluɓe su a wannan ranar, ba za su samu wanda zai kare su daga fushin Allah da azabarsa ba, za su zamanto tamkar an lulluɓe fuskokinsu ne da wani yanki na dare mai tsananin duhu, saboda duhun fuskokinsu. Waɗannan su ne ‘yan wuta masu zama a cikinta har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai kunyata mushirikai a ranar gobe ƙiyama a bainar taron jama’a, domin hakan ya zamo musu wani ƙarin azaba ce da wulaƙanci saboda haɗa Allah da wani da suka yi wajen bauta.

2. Duk masu bautar wasu ba Allah ba, a ranar lahira za su nisanta kansu da su.

3. Duk wata ibada ga Allah da aka gauraya ta da wani abu na shirka ba za ta karɓu ba wajen Allah.

Suratu Yunus (28-30)
وَيَوۡمَ نَحۡشُرُهُمۡ جَمِيعٗا ثُمَّ نَقُولُ لِلَّذِينَ أَشۡرَكُواْ مَكَانَكُمۡ أَنتُمۡ وَشُرَكَآؤُكُمۡۚ فَزَيَّلۡنَا بَيۡنَهُمۡۖ وَقَالَ شُرَكَآؤُهُم مَّا كُنتُمۡ إِيَّانَا تَعۡبُدُونَ٢٨ فَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدَۢا بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمۡ إِن كُنَّا عَنۡ عِبَادَتِكُمۡ لَغَٰفِلِينَ٢٩ هُنَالِكَ تَبۡلُواْ كُلُّ نَفۡسٖ مَّآ أَسۡلَفَتۡۚ وَرُدُّوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ مَوۡلَىٰهُمُ ٱلۡحَقِّۖ وَضَلَّ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ٣٠

28. (Ka tuna) ranar da za mu tara su ga baki ɗaya, sannan mu ce da waɗanda suka yi shirka: “Ku tsaya cak a wurarenku ku da abokan tarayyarku”. Sai kuma mu raba tsakaninsu; sai abokan tarayyarsu kuma su ce: “Ba mu ne kuka kasance kuna bauta wa ba.

29. “To kuma Allah Ya isa shaida tsakaninmu da ku: mu kam lalle mun kasance ba mu ma san kuna bautar mu ba.”

30. A can ne kowane rai zai samu sakamakon abin da ya gabatar (a duniya). An kuma mayar da su zuwa ga Allah Majiɓincinsu na gaskiya; abin da kuma suka kansance suna ƙirƙira ya ɓace musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da Annabi (ﷺ) ranar ƙiyama ne lokacin da Allah zai tattara halittunsa wuri ɗaya don yi musu hisabi, sannan ya kira waɗanda suka yi shirka ya umarce su da cewa, su tsaya cak a wurarensu su da abokan tarayyarsu, sai kuma ya raba tsakaninsu da abokan tarayyarsu, sai su abokan tarayyar su faɗa wa masu bauta musu cewa, su fa a gaskiya ba su suke bauta wa ba; suna bauta wa soye-soyen zukatansu ne kawai tare da shaiɗanunsu waɗanda suka umarce su da su bauta musu. Suka ce Allah ne shaida a tsakaninsu, kuma su ba su ma san da bautar da suka kasance suna yi musu ba.
Allah ya bayyana cewa, a wannan wuri ne a ranar alƙiyama kowane rai zai san abin da ya aikata na alheri ko na sharri, domin zai gan shi rubuce a gabansa kuma a yi masa hisabi a kansa. Kuma an mayar da mushirikai zuwa ga Ubangijinsu na gaskiya don ya yi musu sakayya da adalci, duk kuma abin da suka ƙirƙira na ƙarya ga Allah ya ɓace musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai taƙaita kwararar arziƙinsa ga mutane a kan wata jaha guda ba; yana arzuta su ne arzuƙi mai yalwa ta sama da ƙasa.

2. Mushirikan Larabawa sun amince a kan akwai Allah mahallicin kowa da komai, sai dai suna bautar gumaka ne suna da'awar cewa ta hanyarsu ne za su sami kaiwa wajen Allah kuma su ne masu ceton su a wurinsa.

3. Alƙur'ani yana tabbatar wa da mushirikai cewa, ba za ta yiwu a rarrabe tsakanin yarda da Rububiyyar Allah da kuma Uluhiyyarsa ba, duk wanda ya yarda da cewa, Allah ne Ubangijinsa, kuma mahallicin kowa da kome, to ya zama dole ne ya yarda da cewa shi kaɗai ne abin bauta.

4. Gaskiya da ƙarya kishiyoyin juna ne, ba za su haɗu a wuri guda ba har abada; hakanan shiriya da ɓata su ma kishiyoyin juna ne, ba masu haɗuwa ne ba har abada.

Suratu Yunus (31-33)
قُلۡ مَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ أَمَّن يَمۡلِكُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَمَن يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَيُخۡرِجُ ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّ وَمَن يُدَبِّرُ ٱلۡأَمۡرَۚ فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُۚ فَقُلۡ أَفَلَا تَتَّقُونَ٣١ فَذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمُ ٱلۡحَقُّۖ فَمَاذَا بَعۡدَ ٱلۡحَقِّ إِلَّا ٱلضَّلَٰلُۖ فَأَنَّىٰ تُصۡرَفُونَ٣٢ كَذَٰلِكَ حَقَّتۡ كَلِمَتُ رَبِّكَ عَلَى ٱلَّذِينَ فَسَقُوٓاْ أَنَّهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ٣٣

31. Ka ce: "Wane ne yake arzuta ku ta sama da ƙasa? Ko kuma wane ne mamallakin ji da gani? Kuma wane ne yake fitar da mai rai daga matacce, ya kuma fitar da matacce daga mai rai? Wane ne kuma yake tsara al'amura?" To ai za su ce: "Allah ne." To ka ce: "Yanzu ba za ku kiyaye dokokinsa ba?"

32. To wannan Shi ne Allah Ubangijinku na gaskiya. Bayan gaskiya kuwa babu wani abu sai ɓata. To yaya ake karkatar da ku?

33. Kamar haka ne kalmar Ubangijinka ta tabbata a kan waɗanda suka yi fasiƙanci cewa su ba za su yi imani ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya tambayi mushirikai cewa, wane ne yake arzuta su ta sama da ta ƙasa? Ko kuma wane ne ya mallaki ji da gani? Wane ne kuma da girman ikonsa yake fitar da abu mai rai daga matacce, yake kuma fitar da matacce daga mai rai? Wane ne yake gudanar da al'amuran dukkan halittu, yake sarrafa komai a sama da ƙasa yadda ya ga dama? To duka dai mushirikai za su ce: Ai Allah ne shi kaɗai yake yin duk waɗannan abubuwa. To sai Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, idan haka ne me ya hana su kiyaye dokokinsa su kuma ji tsoron azabarsa?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, to mai yin waɗannan ayyuka shi ne kaɗai wanda ya cancanci a bauta masa, shi ne kuma Ubangijinsu na gaskiya wanda babu shakka dangane da shi. To mene ne kuma bayan gaskiya ta bayyana in ba ɓata ba? Don haka ta ƙaƙa ake juyar da su ba sa fahimtar gaskiya?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda aka karkatar da mushirikai daga kan gaskiya suka ci gaba da aikata shirka, to haka kalmar Allah ta azaba ta tabbata a kan waɗanda suka yi fasiƙanci cewa ba za su yi imani ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai dukkan hujjojin kaɗaitakarsa wajen bauta cikin sigar tambaya, domin ya riga ya san ba su da wata gamsasshiyar amsa da za su iya bayarwa a kai, sai dai su sallama masa a kan amsar da take ta gaskiya wadda kuma za ta ɗaure su.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu kasawar abubuwan bautarsu, wanda hakan yana nuna cewa ,ba su cancanci a bauta musu ba ko kaɗan.

3. Bayanin cewa Allah ne kaɗai mai shiryarwa ga gaskiya amma duk wani mahaluƙi mai buƙatar a shiryar da shi ne, Allah ne kuma mai shiryar da shi, saboda haka bautar Allah ce kaɗai gaskiya ba bautar waninsa ba.

4. Ya wajaba a kan duk wani Musulmi ya san cewa, manufarsa a rayuwa ita ce ya tsarkake zuciyarsa ta hanyar bin gaskiya cikin lamuran aƙidarsa da bin shiriya cikin duk wani aikinsa, ya kuma gina wannan a kan harsashi na ingantaccen ilimi ba kan zato da shaci-faɗi ba.

5. Duk wata aƙida ko wani ilimi da ya ci karo da abin da ya zo a Alƙur'ani da sunnar Manzon Allah (ﷺ) to zato ne marar tushe, wajibi ne kuma a yi watsi da shi.

Suratu Yunus (34-36)

قُلۡ هَلۡ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥۚ قُلِ ٱللَّهُ يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٣٤ قُلۡ هَلۡ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَهۡدِيٓ إِلَى ٱلۡحَقِّۚ قُلِ ٱللَّهُ يَهۡدِي لِلۡحَقِّۗ أَفَمَن يَهۡدِيٓ إِلَى ٱلۡحَقِّ أَحَقُّ أَن يُتَّبَعَ أَمَّن لَّا يَهِدِّيٓ إِلَّآ أَن يُهۡدَىٰۖ فَمَا لَكُمۡ كَيۡفَ تَحۡكُمُونَ ٣٥ وَمَا يَتَّبِعُ أَكۡثَرُهُمۡ إِلَّا ظَنًّاۚ إِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغۡنِي مِنَ ٱلۡحَقِّ شَيۡـًٔاۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ بِمَا يَفۡعَلُونَ ٣٦ قُلۡ هَلۡ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥۚ قُلِ ٱللَّهُ يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٣٤ قُلۡ هَلۡ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَهۡدِيٓ إِلَى ٱلۡحَقِّۚ قُلِ ٱللَّهُ يَهۡدِي لِلۡحَقِّۗ أَفَمَن يَهۡدِيٓ إِلَى ٱلۡحَقِّ أَحَقُّ أَن يُتَّبَعَ أَمَّن لَّا يَهِدِّيٓ إِلَّآ أَن يُهۡدَىٰۖ فَمَا لَكُمۡ كَيۡفَ تَحۡكُمُونَ ٣٥ وَمَا يَتَّبِعُ أَكۡثَرُهُمۡ إِلَّا ظَنًّاۚ إِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغۡنِي مِنَ ٱلۡحَقِّ شَيۡـًٔاۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ بِمَا يَفۡعَلُونَ ٣٦

34. Ka ce: “Shin daga cikin abokan tarayyarku ko akwai wanda yake ƙaga halitta, sannan ya maimaita ta?” Ka ce: “Allah Shi ne Wanda Yake ƙaga halitta sannan Ya maimaita ta. To ta yaya ake kautar da ku?”

35. Ka ce: “Shin daga abokan tarayyarku ko akwai wanda yake shiryarwa zuwa gaskiya?” Ka ce: “Allah Shi ne Yake shiryarwa zuwa ga gaskiya. To yanzu wanda yake shiryarwa zuwa gaskiya shi ya fi cancanta a bi, ko kuwa wanda ba ya shiryarwa sai dai a shiryar da shi? To me ya same ku ne? Yaya kuke wannan hukuncin?

36. Yawancinsu kuma ba abin da suke bi sai zato. Lalle zato ba ya wadatar da komai game da gaskiya. Lalle Allah Masanin abin da suke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) ya tambayi mushirikai masu bautar wasu ba Allah ba cewa, a cikin abubuwan da suke bauta wa ko akwai wanda zai iya ƙagar halittar wani abu, sannan idan wannan abin ya mutu ya sake dawo masa da ransa? To idan ba su da wata amsar da za su iya bayarwa, to shi Annabi (ﷺ) ya amsa musu da cewa, Allah ne kaɗai yake iya ƙagar halitta sannan ya sake dawo mata da rai bayan mutuwa, to amma duk da sun san Allah ne kaɗai zai iya yin hakan gumakansu kuma ba za su iya yi ba, me ya same su ne ba za su bi gaskiya ba? Ta yaya ne kuma ake kawar da su daga gaskiya suka kama ɓata?
Allah kuma ya sake umartar Annabi (ﷺ) da ya tambaye su cewa, shin cikin allolin da suke bauta wa ko akwai wanda yake shiryarwa zuwa ga gaskiya? Idan ba su da amsa, to shi ya amsa musu da cewa, Allah ne kaɗai mai shiryarwa zuwa ga gaskiya. To yanzu ashe wanda yake mai shiryarwa zuwa ga gaskiya, watau Allah, shi ne ya fi cancantar a bauta masa ko kuma allolinsu waɗanda ba sa iya shiryar da kowa zuwa ga gaskiya sai dai su a shiryar da su, su ne suka kamata a bauta musu ba Allah ba? Me ya samu mushirikai ne, yaya suke irin wannan ɗanyen hukunci?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, su dai waɗannan mushirikai ba komai suke bi ba wajen shirkarsu da Allah sai zunzurutun zato marar tushe kuma marar tabbas; shi kuwa zato ba ya wadatar da komai game da tabbatar da gaskiya. Lalle Allah masanin duk abin da suke aikatawa ne, kuma zai yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin cewa babu wani mahaluƙi da ya isa ya ƙago wani abu kamar Alƙur’ani wajen fasaharsa da hikimarsa da tsarin zubinsa da salon maganarsa da sauransu.

2. Bai dace ga wani ya yi saurin ƙaryata wani al’amari ko karɓar sa ba tare da ya fahimce shi ba.

3. Kafirai ba su zama ɗaya ba wajen ƙanƙame aƙidarsu; daga cikinsu akwai waɗanda suke yin watsi da aƙidarsu ta kafirci bayan gaskiya ta bayyana gare su; akwai kuma waɗanda suke girman kai su ƙi karɓar gaskiya, su dogewa a kan ƙarya.

Suratu Yunus (37-40)

وَمَا كَانَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ أَن يُفۡتَرَىٰ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِن تَصۡدِيقَ ٱلَّذِي بَيۡنَ يَدَيۡهِ وَتَفۡصِيلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَا رَيۡبَ فِيهِ مِن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٣٧ أَمۡ
يَقُولُونَ ٱفۡتَرَىٰهُۖ قُلۡ فَأۡتُواْ بِسُورَةٖ مِّثۡلِهِۦ وَٱدۡعُواْ مَنِ ٱسۡتَطَعۡتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٣٨ بَلۡ كَذَّبُواْ بِمَا لَمۡ يُحِيطُواْ بِعِلۡمِهِۦ وَلَمَّا يَأۡتِهِمۡ
تَأۡوِيلُهُۥۚ كَذَٰلِكَ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلظَّٰلِمِينَ ٣٩ وَمِنۡهُم مَّن يُؤۡمِنُ بِهِۦ وَمِنۡهُم مَّن لَّا يُؤۡمِنُ بِهِۦۚ وَرَبُّكَ أَعۡلَمُ
بِٱلۡمُفۡسِدِينَ ٤٠

37. Wannan Alƙur'ani bai yiwuwa a ƙage shi daga (tunanin) wani wanda ba Allah ba, sai dai (shi) gaskatawa ne ga abin da ya gabace shi (na littattafan da aka saukar), kuma bayani ne dalla-dalla na hukunce-hukuncen (da Allah ya saukar); babu kokwanto a cikinsa cewa daga Ubangijin talikai yake.

38. Ko kuma cewa suke yi: "Ƙagar sa ya yi ne?" Ka ce: "To ku kawo sura (ɗaya tal) irinsa, kuma ku kirawo wanda duk za ku iya (ya taimaka muku) wanda ba Allah ba idan kun kasance masu gaskiya!"

39. A'a, ba haka ba ne, sun dai ƙaryata abin da ba su da iliminsa ne, kuma har yanzu haƙiƙanin fassararsa ba ta zo musu ba. Kamar haka ne waɗanda suka gabace su suka ƙaryata. To duba ka ga yadda ƙarshen azzalumai ya zama.

40. Daga cikinsu kuma akwai wanda yake yin imani da shi (Alƙur'ani), akwai kuma wanda ba ya yin imani da shi. Ubangijinka kuma Shi ne Mafi sanin maɓarnata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, ba zai yiwu a ce wannan Alƙur'anin ƙarya ne, wani ne ya ƙago shi ba Allah ba. A'a, Alƙur'ani littafi ne da Allah ya saukar, wanda kuma yake gaskata duk littattafan da suka gabace shi waɗanda Allah ya saukar ga annabawansa, sannan yana bayanin abin da Allah ya wajabta wa wannan al'umma na aƙida da hukunce-hukunce da bayanin labarai daban-daban, wanda babu shakka a cikinsa, saukakke ne daga Ubangijin talikai.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da cewa; su mushirikai cewa suke yi wai Annabi Muhammadu (ﷺ) shi ne ya ƙagi Alƙur'ani, to idan haka ne, shi Annabi (ﷺ) ya neme su, su ma su ƙago ko da sura ɗaya ce tal kamar ta Alƙur'ani, domin ai su ma Larabawa ne ƙwararru masu magana da harshen Larabci kamarsa, su yi hakan idan har suna da gaskiya a kan cewa shi ne ya ƙago Alƙur'ani.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce, abin ba kamar yadda suke riyawa ba ne, kawai dai sun ƙaryata Alƙur'ani ne don ba su laƙanci abin da ya ƙunsa na ilimi ba, kuma suna ganin har yanzu kashedin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi musu na saukar azaba saboda ƙaryata Alƙur'ani da suka yi, bai same su ba. To kamar haka ne waɗanda suka gabace su cikin kafirai suka ƙaryata annabawansu. Allah kuma ya umarci Annabi (ﷺ) ya duba ya ga yadda ƙarshen azzalumai masu ƙaryata ayoyin Allah cikin al 'ummun da suka gabata ya zama.
Sai kuma ya bayyana cewa, daga cikin su waɗannan mushirikan akwai wanda zai yi imani nan gaba ya tuba ya bar shirka, akwai kuma wanda ba zai yi imani ya tuba ba, zai yi ta zama a kan kafircinsa har mutuwa. Allah ya tabbatar da cewa, shi ya fi kowa sanin maɓarnata kuma zai yi maganin su duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin cewa Allah ba ya kama wani da laifin wani.

2. Shiriya daga Allah take, shi ne yake shiryar da wanda ya ga dama.

3. Duba zuwa ga kyawawan halayen Manzon Allah da nagartattun ayyukansa yana jagoranci zuwa ga fahimtar gaskiyar annabcinsa da ingancin abin da ya zo da shi daga Allah.

4. Ɓacewar kafirai da rashin amfanuwarsu da jinsu da ganinsu wajen gane shiriya ba ya faru ne don Allah ya zalunce su ba; haka ya biyo bayan tsattsauran ra'ayinsu ne da girman kansu da dagewarsu a kan bin kafirci, don haka su ne suka zalunci kawunansu, Allah bai zalunce su da komai ba.

Suratu Yunus (41-44)

وَإِن كَذَّبُوكَ فَقُل لِّي عَمَلِي وَلَكُمْ عَمَلُكُمْ ۖ أَنتُم بَرِيٓـُٔونَ مِمَّآ أَعْمَلُ وَأَنَا۠ بَرِيٓءٌ مِّمَّا تَعْمَلُونَ ﴿٤١﴾ وَمِنْهُم مَّن يَسْتَمِعُونَ إِلَيْكَ ۚ أَفَأَنتَ تُسْمِعُ ٱلصُّمَّ وَلَوْ كَانُوا۟ لَا يَعْقِلُونَ ﴿٤٢﴾ وَمِنْهُم مَّن يَنظُرُ إِلَيْكَ ۚ أَفَأَنتَ تَهْدِى ٱلْعُمْىَ وَلَوْ كَانُوا۟ لَا يُبْصِرُونَ ﴿٤٣﴾ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَظْلِمُ ٱلنَّاسَ شَيْـًٔا وَلَٰكِنَّ ٱلنَّاسَ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴿٤٤﴾

41. Idan kuwa suka ƙaryata ka, to ka ce: ‘‘Aikina nawa ne ku ma aikinku naku ne. Ku babu ruwanku da abin da nake aikatawa, ni ma kuma babu ruwana da abin da kuke aikatawa.’’

42. Daga cikinsu akwai waɗanda suke sauraron ka. Yanzu kai za ka iya jiyar da kurame ko da ba su da hankali?

43. Daga cikinsu kuma akwai wanda yake ƙura maka ido. Yanzu kai za ka iya shiryar da makafi ko da ba sa gani?

44. Lalle Allah ba Ya zaluntar mutane da komai, sai dai mutane kawunansu kawai suke zalunta.
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, idan mushirikai suka ƙaryata shi, suka kuma ƙi yin imani da abin da ya zo musu da shi na gaskiya, to ya faɗa musu cewa, aikinsa nasa ne ba za a kama su da laifinsa ba; su ma kuma ayyukansu nasu ne, ba za a kama shi da laifukansu ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, daga cikin kafirai akwai masu sauraron sa yayin da yake karanta Alƙur’ani ko yake magana da su, to amma zukatansu a rufe suke, a lokacin ba sa amfana da komai cikin abin da suke sauraro, su da kurame a lokacin ɗaya suke babu bambanci, to shin Annabi (ﷺ) zai iya jiyar da wanda yake kurma wani abu, musamman idan kurumcin ya haɗu da rashin hankali?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ƙara da cewa, cikinsu har ila yau akwai waɗanda suke ƙura masa idanu idan yana bayani kamar suna ganin hasken gaskiya da ke tare da shi, to amma fa da su da makafi a lokacin ɗaya suke babu bambanci. To shin Annabi (ﷺ) zai iya shiryar da makafi ya nuna musu hanya ko da kuwa ba sa ganin komai kuma babu wata basira tare da su?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lalle shi ba ya zaluntar bayinsa da komai, sai dai su mutane su ne suke zaluntar kawunansu da kafirci da saɓon Allah da suke tafkawa, don haka suka cancanci azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rage dogon buri daga zukatan muminai domin hakan shi ne zai sa su fahimci duniya rayuwa ce taƙaitacciya mai ƙarewa da gaggawa, don haka dole ne su yi gaggawar yin guzurin ayyuka na ƙwarai domin ranar tafiya.

2. Al’amarin wannan addini duka a hannun Allah yake, babu wani abu na zartar da hukuncin halaka ko azaba a hannun Manzon Allah (ﷺ), Allah ne zai zartar da abin da ya ga dama, ko dai ya gaggauto wa masu ƙaryata shi da cutar da shi azaba tun yana raye ya ga abin da ya same su da idonsa, ko kuma ya gama isar da saƙonsa ya komo ga Allah ba tare da an nuna masa makomar masu ƙaryata shi ba. Don haka babban abin da yake kan duk wani mai kira zuwa ga Allah shi ne isar da saƙon Allah kawai, sakamako kuwa yana hannun Allah ne shi kaɗai.

3. Wannan aya ta 46 tana nuna cewa, Allah zai nuna wa Annabinsa (ﷺ) irin wulaƙancin da zai sami kafirai tun yana da rai, sannan bayan ya bar duniya Allah zai ƙara musu ƙasƙanci da wulaƙanci. Kuma wannan duk ya faru a lokacin rayuwar Manzon Allah (ﷺ) da bayan wafatinsa, sannan abin da zai faru gare su na azaba da ƙasƙanci a ranar alƙiyama shi ya fi tsanani da yawa.

4. Duk wata al'umma da ta gabata Allah ya aiko musu da manzo domin ya kirawo su zuwa ga bautar Allah shi kaɗai da barin bautar waninsa.

5. Gargaɗi a kan haɗarin saɓa wa Annabi (ﷺ).

Suratu Yunus (45-47)

وَيَوْمَ يَحْشُرُهُمْ كَأَن لَّمْ يَلْبَثُوٓاْ إِلَّا سَاعَةً مِّنَ ٱلنَّهَارِ يَتَعَارَفُونَ بَيْنَهُمْۚ قَدْ خَسِرَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِلِقَآءِ ٱللَّهِ وَمَا كَانُواْ مُهْتَدِينَ ﴿٤٥﴾ وَإِمَّا نُرِيَنَّكَ
بَعْضَ ٱلَّذِى نَعِدُهُمْ أَوْ نَتَوَفَّيَنَّكَ فَإِلَيْنَا مَرْجِعُهُمْ ثُمَّ ٱللَّهُ شَهِيدٌ عَلَىٰ مَا يَفْعَلُونَ ﴿٤٦﴾ وَلِكُلِّ أُمَّةٍ رَّسُولٌۖ فَإِذَا جَآءَ رَسُولُهُمْ قُضِىَ بَيْنَهُم بِٱلْقِسْطِ
وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿٤٧﴾

45. Ranar da zai tattara su kuwa (za su ga) kamar ba su zauna ba sai wani ɗan lokaci na rana da suke gane junansu (a cikinsa). Haƙiƙa waɗanda suka ƙaryata gamuwa da Allah sun taɓe, ba su kuma zamanto shiryayyu ba.

46. Ko dai Mu nuna maka sashin abin da Muke musu alkawarinsa ko kuma Mu karɓi ranka, to makomarsu dai gare Mu take, sannan Allah Yana sane da abin da suke aikatawa.

47. Kowacce al'umma kuma tana da manzo. To idan manzonsu ya zo (suka ƙaryata shi) to sai a yi hukunci a tsakaninsu da adalci, su kuma ba za a zalunce su ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, a ranar da zai tattara kafirai gaba ɗaya a wuri guda domin yi musu hisabi, za su ga kamar ba su taɓa zama a duniya ba sai ɗan lokaci na yini. A ranar za su riƙa gane junansu kamar yadda suke yi a duniya. Don haka waɗanda suka ƙaryata haɗuwa da Allah sun yi hasarar ladansu da gidan Aljanna, kuma ba su zamanto shiryayyu ba.
Sannan Allah ya bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, ko dai ya gaggauto wa da kafirai uƙubarsu tun a duniya domin ya nuna masa wani ɓangare na alƙawarinsa da yake musu na azaba, ko kuma ya karɓi ransa kafin ya nuna masa hakan, to dai ko ma mene ne, makomarsu gaba ɗaya zuwa ga Allah ne, kuma Allah yana ganin abin da suke aikatawa a nan duniya, don haka zai yi musu sakayya a kansa gobe ƙiyama.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kowace al'umma tana da manzon da ya zo mata daga Allah yana kiran ta zuwa ga yin imani da bautar Allah shi kaɗai. To idan wannan manzon ya zo wa wannan al'umma a ranar alƙiyama domin ya ba da shaida a kansu, a lokacin Ubangiji zai yi musu hukunci na adalci ba tare da ya zalunce su ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wa'azi da gargaɗi ga masu kiran sunan Annabi (ﷺ) suna neman agajinsa lokacin da wata musiba ta auka musu wadda babu mai iya yi musu maganinta sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Wannan matsayi ne na Allah shi kaɗai mahaliccin duk duniya, wanda kuma shi ne ya halicci annabawa da salihai da sauran halittu, shi ne mai arzuta su mai raya su ya kashe su, to me ya sa ba za su nema wajensa shi kaɗai ba, su bar nema wajen wani annabi ko mala'ika ko wani waliyyi?

2. Duk wani mahaluƙi ba ya mutuwa sai wa'adinsa ya cika.

3. Ba a son yawan rantsuwa. Amma yakan zama mustahabbi idan akwai wata masalaha ta shari'a a cikin yin ta, kamar yadda Allah ya umarci Annabinsa da ya rantse da shi don jan hankalin abokan maganarsa masu jayayya da shi.

Suratu Yunus (48-53)

وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٤٨ قُل لَّآ أَمۡلِكُ لِنَفۡسِي ضَرّٗا وَلَا نَفۡعًا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۗ لِكُلِّ أُمَّةٍ أَجَلٌۚ إِذَا جَآءَ أَجَلُهُمۡ فَلَا يَسۡتَأۡخِرُونَ سَاعَةٗ وَلَا يَسۡتَقۡدِمُونَ ٤٩ قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِنۡ أَتَىٰكُمۡ عَذَابُهُۥ بَيَٰتًا أَوۡ نَهَارٗا مَّاذَا يَسۡتَعۡجِلُ مِنۡهُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٥٠ أَثُمَّ إِذَا مَا وَقَعَ ءَامَنتُم بِهِۦٓۚ ءَآلۡـَٰٔنَ وَقَدۡ كُنتُم بِهِۦ تَسۡتَعۡجِلُونَ ٥١ ثُمَّ قِيلَ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ ذُوقُواْ عَذَابَ ٱلۡخُلۡدِ هَلۡ تُجۡزَوۡنَ إِلَّا بِمَا كُنتُمۡ تَكۡسِبُونَ ٥٢ ۞وَيَسۡتَنۢبِـُٔونَكَ أَحَقٌّ هُوَۖ قُلۡ إِي وَرَبِّيٓ إِنَّهُۥ لَحَقّٞۖ وَمَآ أَنتُم بِمُعۡجِزِينَ ٥٣

48. Suna kuma cewa: "To yaushe ne wannan alƙawari (zai zo) idan kun kasance masu gaskiya?"

49. Ka ce: "Ba na mallakar wata cuta, ko wani amfani ga kaina sai dai abin da Allah Ya ga dama. Kowacce al'umma tana da lokacin (da aka iyakance mata). Idan lokacin nasu ya yi, to ba za su yi jinkiri na sa'a guda ba, kuma ba za su gaggauto ba."

50. Ka ce: "Yanzu ku ba ni labari (yadda za ku yi) idan azabar Allah ta zo muku da daddare ko da rana; mene ne masu laifi suke yi wa gaggawar zuwansa?

51. "Shin sai idan (azabar) ta afka (muku) ne za ku yi imani da Shi (Allah)? Sai yanzu ne, alhali kuwa da can kun kasance kuna neman gaggautowarta?"

52. Sannan aka ce da waɗanda suka yi zalunci: "Ku ɗanɗani azaba mai dawwama; shin za a saka muku (da wani abu ne) in ban da abin da kuka kasance kuna aikatawa?."

53. Suna kuma tambayar ka cewa: "Yanzu (batun azabar nan) gaskiya ne kuwa?" Ka ce: "I mana, na ko ranste da Allah lalle shi gaskiya ne; ba kuma za ku kuɓuce ba."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin tambayar da mushirikai suke yi wa Annabi (ﷺ) da mabiyansa cewa, yaushe ne azabar Allah da suke yi musu alƙawarinta za ta zo musu idan sun kasance masu gaskiya?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ba su amsa cewa, shi a matsayinsa na Annabi ba shi da ikon ya cutar da kansa ko ya amfanar da kansa da komai sai abin da Allah ya ga dama ya ƙaddara masa, kuma ba shi da ikon ya zo musu da azabar da suke neman ya zo musu da ita, sai dai su sani cewa, kowacce al'umma tana da lokacin da aka iyakance mata na rayuwarta; idan wannan lokacin ya yi to ba za a jinkirta musu ba daidai da sa'a guda kuma ba za a gabato musu da ajalinsu ba kafin lokacinsa.
Ya kuma umarce shi ya faɗa musu cewa, yanzu idan azabar Allah ta zo musu da daddare ko da rana, mene ne waɗannan masu laifi za su amfana da gaggauto da zuwanta in ban da sharri wanda kuma ba za su iya kauce masa ba idan ya zo? Kuma shin wai sai idan azabar ta auka musu ne sannan za su yi imani lokacin da imani ba zai yi musu amfani ba? Sai yanzu ne za su yi imani alhalin a da suna nema a gaggauto da azabar wadda suke ƙaryatawa?

Sannan Allah ya bayyana cewa, a ranar alƙiyama za a faɗa wa waɗanda suka zalunci kawunansu cewa, su ɗanɗani azaba ta har abada, domin ai ba za a saka musu da komai ba sai da abin da suka kasance suna aikatawa a nan duniya.
Sannan Allah ya bayyana cewa, mushirikai suna tambayar Annabi (ﷺ) cewa, azabar da aka yi musu alƙawarin zuwanta gaskiya ne kuwa? To Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya ba su amsa da "I mana, na ko ranste da Allah lalle shi gaskiya ne, ba kuma za ku kuɓuce ba". Watau idan ya zo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Amfanarwa da cutarwa da lada da azaba duk za su kasance ne gwargwadon kyawawan ayyukan kowa ko munanansu.

2. Duk abin da mutum yake taƙama da shi a duniya na dukiya ko mulki ko 'ya'ya ba za su amfane shi da komai ba ranar alƙiyama sai aikinsa nagari.

3. Da yawa mutane sukan manta da cewa duk abin da yake sammai da ƙasa mallakin Allah ne, don haka suke buƙatar a riƙa tunatar da su a kan hakan ana jawo hankalinsu don su faɗaku.

Suratu Yunus (54-56)

وَلَوْ أَنَّ لِكُلِّ نَفْسٍ ظَلَمَتْ مَا فِي ٱلْأَرْضِ لَٱفْتَدَتْ بِهِۦ ۗ وَأَسَرُّوا۟ ٱلنَّدَامَةَ لَمَّا رَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ ۖ وَقُضِىَ بَيْنَهُم بِٱلْقِسْطِ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿٥٤﴾ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۗ أَلَآ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٥٥﴾ هُوَ يُحْىِۦ وَيُمِيتُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٥٦﴾ وَلَوْ أَنَّ لِكُلِّ نَفْسٍ
ظَلَمَتْ مَا فِي ٱلْأَرْضِ لَٱفْتَدَتْ بِهِۦ ۗ وَأَسَرُّوا۟ ٱلنَّدَامَةَ لَمَّا رَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ ۖ وَقُضِىَ بَيْنَهُم بِٱلْقِسْطِ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿٥٤﴾ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ۗ أَلَآ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٥٥﴾ هُوَ يُحْىِۦ وَيُمِيتُ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٥٦﴾

54. Da a ce kowane rai da ya yi zalunci ya mallaki duk abin da yake bayan ƙasa, to lalle da ya fanshi kansa da shi. Suka kuwa ɓoye nadama a lokacin da suka ga azaba; an kuma yi hukunci tsakaninsu na adalci; ba kuma za a zalunce su ba.

55. A saurara, lalle duk abin da yake sammai da ƙasa na Allah ne. A saurara, lalle alƙwarin Allah gaskiya ne, sai dai kuma yawancin mutane ba su sani ba.

56. Shi ne Yake rayawa Yake kuma kashewa, kuma wurinsa za a mai da ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayani cewa, da a ce kowane rai da ya aikata kafirci ko shirka da Allah ya mallaki duk abin da yake bayan ƙasa, to da ya bayar da shi gaba ɗaya ranar alƙiyama a matsayin dukiyar fansar kansa daga azabar Allah, da ya san za a karɓa daga wajensa. Kafirai kuma za su riƙa ɓoye nadamarsu da takaicinsu a kan kafircinsu lokacin da suka ga azabar Allah ranar alƙiyama, suka tabbatar sai ta auka musu. Allah kuma ya yi hukunci a tsakaninsu da adalci ba tare da ya zalunce su ba da komai.
Sai ya bayyana cewa, duk abin da yake cikin sammai da wanda yake bayan ƙasa haƙiƙa duk nasa ne, kuma lalle alƙawarinsa gaskiya ne yana nan tafe ba makawa, sai dai yawancin waɗannan mushirikan ba su sani ba.
Shi ne kuma Ubangiji Allah Ɗaya tal mai kashewa mai rayawa, kuma zuwa gare shi kaɗai ɗaukacin mutane makomarsu take, don haka zai yi musu sakayya a ranar alƙiyama a kan ayyukansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani magani ne ga dukkan cututtukan zukata waɗanda suka haɗa da miyagun aƙidu da miyagun halaye da hassada. Cutar zuciya ta fi cutar jiki haɗari, domin cutar jiki iyakarta kashewa a nan duniya, amma cutar zuciya ta addini da miyagun halaye ba ta rabuwa da mutum har bayan mutuwa, wataƙila ma ta jawo masa shiga wahala ta har abada.

2. Alƙur'ani littafi ne da ya ƙunshi siffofi da dama, daga cikinsu akwai guda huɗu da aka ambata a wannan ayar, watau kasansewarsa wa'azi, kuma waraka ga abin da yake cikin zukata, kuma shiriya, sannan rahama ga muminai.

3. Har kullum yana da kyau ga bawa ya riƙa farin ciki da ni'imar imani da Alƙur'ani da Allah ya yi masa, domin yin haka alama ce da ke nuna kamalar imani.

4. Duk wata ni'ima ta duniya komai girmanta a idanun mutane, to ba a bakin komai take ba idan an kwatanta ta da ni'imar imani da shiriya.

5. Mai ilimi bai dace gare shi ya riƙa nuna ɓacin ransa a kan abin da aka hore wa wasu na ƙyale-ƙyalen duniya ba.

Suratu Yunus (57-58)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدْ جَآءَتْكُم مَّوْعِظَةٌ مِّن رَّبِّكُمْ وَشِفَآءٌ لِّمَا فِى ٱلصُّدُورِ وَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿٥٧﴾ قُلْ بِفَضْلِ ٱللَّهِ وَبِرَحْمَتِهِۦ فَبِذَٰلِكَ فَلْيَفْرَحُوا۟ هُوَ خَيْرٌ مِّمَّا يَجْمَعُونَ ﴿٥٨﴾

57. Ya ku mutane, haƙiƙa gargaɗi ya zo muku daga Ubangijinku da kuma waraka ga abin da yake cikin zukatanku, kuma shiriya ne da rahama ga muminai.

58. Ka ce: "Da falalar Allah da rahamarsa, sai su yi farin ciki da wannan; shi ya fi alheri daga abin da suke tarawa (na dukiya)."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ne ga mutane baki ɗaya domin sanar da su cewa, Alƙur'ani ya zo musu daga Ubangijinsu wanda yake ƙunshe da wa'azi da umarni da hani, kuma shi ne waraka ga cututtukan zukata irin su sha'awa da ƙullaci da hassada, kuma shiriya ne ga duk wanda ya yi riƙo da shi, zai kuma kuɓutar da shi daga halaka. Haka kuma shi rahama ce ga muminai domin shi ne zai tabbatar musu da duk wani alheri da amfani a rayuwar duniya da ta lahira.
Sannan Allah ya umarci Annabi (ﷺ) da ya umarci muminai su yi farin ciki da murna a bisa falalar Allah, watau imani da Alƙur'ani ba da wani jin daɗi na duniya mai ƙarewa ba, wannan shi ne ya fi musu alheri fiye da abin da suke tarawa na ƙyale-ƙyalen duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu wani mai hurumin halattawa ko haramtawa sai Allah shi kaɗai mahalicci.

2. Duk wanda ya ba wa kansa damar halattawa ko haramtawa ba tare da wani dalili daga Allah ba, to wannan ya tabbata cikakken mai ƙaga wa Allah ƙarya, kuma tabbas zai gamu da uƙubarsa a ranar alƙiyama.

3. Asalin hukuncin abin da Allah ya halitta wa ɗan'adam a sama ko a ƙasa shi ne halacci sai in an sami dalilin haramcinsa.

Suratu Yunus (59-60)

قُلْ أَرَءَيْتُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ لَكُم مِّن رِّزْقٍ فَجَعَلْتُم مِّنْهُ حَرَامًا وَحَلَٰلًا قُلْ ءَآللَّهُ أَذِنَ لَكُمْ أَمْ عَلَى ٱللَّهِ تَفْتَرُونَ ﴿٥٩﴾ وَمَا ظَنُّ ٱلَّذِينَ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَشْكُرُونَ ﴿٦٠﴾

59. Ka ce (da su): "Ku ba ni labarin abin da Allah Ya saukar muku na arziki, sannan kuka mayar da wani haram wani kuma halal". Ka ce: "Yanzu Allah ne Ya yi muku izinin (yin haka), ko kuwa Allah kuke yi wa ƙage ne?"

60. Mene ne kuma tsammanin waɗanda suke yi wa Allah ƙagen ƙarya a ranar alƙiyama? Lalle Allah Ma'abocin falala ne ga mutane, sai dai kuma yawancinsu ba sa godewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya tambayi mushirikai game da arziƙin da Allah ya ba su na dabbobi da kayan amfanin gona, amma kuma sai suka ware wasu suka halatta wa kawunansu, suka kuma haramta wasu ga kawunansu. To wai shin Allah ne ya ba su damar su halatta waɗanda suka halatta, su kuma haramta waɗanda suka haramta, ko kuwa dai ƙarya ce suke ƙaga wa Allah? Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin tsananin narkonsa gare su a kan ƙaryar da suke ƙaga masa da cewa, me suke tsammanin zai yi musu a ranar alƙiyama, shin suna zaton zai ƙyale su ne hakanan ba tare da ya azabtar da su ba? A'a, ba haka ne ba, uƙubarsu a ranar mai tsananin gaske ce saboda ƙaryar da suke yi wa Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, falalarsa ga mutane mai yawa ce, daga cikin falalarsa akwai hore wa bayinsa ni'imomi masu yawa a duniya, yake kuma saurara wa masu laifi ba tare da ya gaggauto yi musu azaba ba; sai dai yawancin mutane ba sa gode wa waɗannan ni'imomi da ya yi musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halarto da cewa Allah yana tare da bawansa a koyaushe yana ganin abin da yake aikatawa zai ƙara dasa masa tsoron sa a zuciyarsa.

2. Duk al'amuran Manzon Allah (ﷺ) manya-manya ne, hatta ayyukansa na al'ada, domin shi ne kyakkyawan abin koyi cikin komai.

3. Waliyyan Allah na gaskiya su ne waɗanda suka haɗa siffofin nan biyu: Imani da taƙawa. Don haka duk wanda ya yi imani kuma ya zamanto mai taƙawa, watau mai kiyaye dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to yana da walittaka gwargwadon imaninsa da taƙawarsa.

4. Duk wanda ba ya aikata abin da Allah ya wajabta masa, ba ya barin abin da aka haramta masa, to wannan ba ya daga cikin waliyyan Allah masu taƙawa.

5. Duk wanda ya yi daʾawar cewa ayyukan ibada ko hukunce-hukuncen shariʾa suna sauka daga kan wasu waliyyai ta yadda haram zai halatta a gare su, to wannan ya ƙaryata Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Manzonsa (ﷺ).

6. Masu taƙawa ba za su gamu da wani firgici ko tsoro ba a farfajiyar alƙiyama.

Suratu Yunus (61-64)

وَمَا تَكُونُ فِي شَأۡنٖ وَمَا تَتۡلُواْ مِنۡهُ مِن قُرۡءَانٖ وَلَا تَعۡمَلُونَ مِنۡ عَمَلٍ إِلَّا كُنَّا عَلَيۡكُمۡ شُهُودًا إِذۡ تُفِيضُونَ فِيهِۚ وَمَا يَعۡزُبُ عَن رَّبِّكَ مِن مِّثۡقَالِ ذَرَّةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِي ٱلسَّمَآءِ وَلَآ أَصۡغَرَ مِن ذَٰلِكَ وَلَآ أَكۡبَرَ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٍ ٦١ أَلَآ إِنَّ أَوۡلِيَآءَ ٱللَّهِ لَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٦٢ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ٦٣ لَهُمُ ٱلۡبُشۡرَىٰ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِۚ لَا تَبۡدِيلَ لِكَلِمَٰتِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٦٤

61. Kuma babu wani alʾamari da (kai Annabi) kake zamantowa cikinsa, babu kuma wani abu na Alƙurʾani da kake karantawa, kuma babu wani abu da kuke aikatawa (kai da alʾummarka), sai Mun zamanto Muna kallon ku lokacin da kuke kutsawa cikinsa. Kuma babu wani abu da yake ɓoye wa Ubangijinka daidai da ƙwayar komayya, a ƙasa ko a sama ko kuma mafi ƙanƙanta ko mafi girma daga wancan (abin) sai fa yana cikin litttafi mabayyani (Lauhul-Mahafuzu).

62. A saurara, lalle waliyyan Allah babu wani tsoro a gare su, kuma ba za su yi wani baƙin ciki ba.

63. (Su ne) waɗanda suka yi imani kuma suka kasance masu kiyaye dokokin Allah.

64. Suna da albishir a rayuwar duniya da kuma ta lahira. Babu wani sauyi ga kalmomin Allah. Wannan shi ne babban rabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da Annabi (ﷺ) cewa, babu wani aiki da zai zamanto a cikinsa, ko wata sura ta Alƙurʾani da zai karanta, ko abin da mutane za su aikata na alheri ko na sharri, babba ko ƙarami mai yawa ko kaɗan, face Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ganin duk abin da yake gudana lokacin da suke aiwatar da shi, kuma zai kiyaye musu shi, ya yi musu sakayya a kai. Hakanan babu abin da yake ɓoye wa Allah komai ƙanƙantarsa, ko da ƙwayar komayya ne, a sama ko a ƙasa, ko ma abin da bai kai haka ba ko ya fi hakan, face duk wannan abu yana nan rubuce a cikin Lauhul-Mahfuzu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ko su wane ne waliyyansa, watau masoyansa, waɗanda yake son su yake taimakon su a koyaushe, ya bayyana cewa waɗannan bayin Allah na ƙwarai babu wani tsoro a tare da su game da abin da za su iske ranar alƙiyama, kuma ba za su yi wani baƙin ciki ba dangane da abin da za su bari nan duniya.
Sai ya bayyana siffofin waɗannan waliyyai da abin da suka yi suka cancanci wannan babban matsayi a wurinsa. Ya ce su ne waɗanda suka yi imani da duk abin da ya wajaba a kansu su yi imani da shi, kuma suka zamanto masu kiyaye dokokin Allah, ta hanyar aikata umarninsa da kauce wa haninsa.
Sannan ya bayyana sakamakonsu da cewa, suna da albishir daga Allah a rayuwarsu ta duniya da kuma rayuwarsu ta lahira. Babu kuma wani sauyi daga maganar Allah, kuma babu saɓa wa alƙawari a wurinsa. Wannan shi ne babban rabo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nusantarwa ga duk wani mai kira zuwa ga Allah a kan ya yi haƙuri da kau da kai daga irin baƙaƙen maganganu ko ɓata suna da za a fuskance shi da su.

2. Girma duka na Allah ne, don haka ana samun sa ne ta hanyar yi masa biyayya da kiyaye dokokinsa.

3. Duk masu bin wasu ba Allah ba, to suna tafiya ne a kan shaci-fadi da zato maras tushe.

Suratu Yunus (65-66)

وَلَا يَحۡزُنكَ قَوۡلُهُمۡۘ إِنَّ ٱلۡعِزَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًاۚ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٦٥ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَمَا يَتَّبِعُ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ شُرَكَآءَۚ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَإِنۡ هُمۡ إِلَّا يَخۡرُصُونَ ٦٦

65. Kada kuma wata maganarsu ta bakanta maka rai. Lalle girma gaba dayansa na Allah ne. Shi Mai ji ne, Masani.

66. Ku saurara, lalle duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin kasa na Allah ne. Wadanda suke bauta wa wani ba Allah ba, ba ababen tarayya (na gaskiya) suke bi ba. Ba abin da suke bi sai mummunan zato, kuma ba abin da suke yi sai shaci-fadi.

A wadannan ayoyi Allah (Mai tsarki da daukaka) yana lallashin Annabi (ﷺ) ne dangane da abin da kafirai suke fada masa na bakaken maganganu da karyata shi a kan sakon da ya zo musu da shi. Allah yana cewa, kada maganarsu da izgilinsu su bakanta masa rai, domin girma da daukaka duka na Allah ne shi kadai a duniya da lahira; shi ne mai kare shi daga duk wata cuta da makircinsu, kuma shi mai jin duk abin da yake fita daga bakunansu ne, masani ne game da duk ayyukansu, don haka zai yi musu sakayya a kai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da daukaka) ya bayyana cikakken ikonsa mai nuna zai iya yin duk abin da ya ga dama, watau kasancewar duk abin da yake sammai da wanda yake kasa nasa ne shi kadai ba ya da abokin tarayya a ciki. Kuma su masu bautar wasu abubuwan tarayya ba Allah ba me suke bi ne? Ba komai suke bi ba sai zato ba tare da wani dalili ba, kuma ba komai suke fada ba sai karya suna jingina wa Allah.

Daga wadannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwadaitarwa a kan yin nazari da tunani cikin gudanar dare da rana tutur.

2. Allah shi ne mai cikakkiyar wadata, kuma mamallakin sammai da kasa, don haka wanda ya siffantu da wadannan siffofi ba zai bukaci da ba.

3. Haramcin magana a kan addini ba tare da ilimi ba.

4. Tsananin azabar da za a yi wa mai kaga wa Allah karya a lahira.

Suratu Yunus (67-70)

هُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيۡلَ لِتَسۡكُنُواْ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبۡصِرًاۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَسۡمَعُونَ ٦٧ قَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدٗا سُبۡحَٰنَهُۥۖ هُوَ ٱلۡغَنِيُّۖ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ إِنۡ عِندَكُم مِّن سُلۡطَٰنِۭ بِهَٰذَآۚ أَتَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٦٨ قُلۡ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَفۡتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ لَا يُفۡلِحُونَ ٦٩ مَتَٰعٞ فِي ٱلدُّنۡيَا ثُمَّ إِلَيۡنَا مَرۡجِعُهُمۡ ثُمَّ نُذِيقُهُمُ ٱلۡعَذَابَ ٱلشَّدِيدَ بِمَا كَانُواْ يَكۡفُرُونَ ٧٠ هُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيۡلَ لِتَسۡكُنُواْ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبۡصِرًاۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَسۡمَعُونَ ٦٧ قَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدٗا سُبۡحَٰنَهُۥۖ هُوَ ٱلۡغَنِيُّۖ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ إِنۡ

عِندَكُم مِّن سُلۡطَٰنِۭ بِهَٰذَآۚ أَتَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٦٨ قُلۡ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَفۡتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ لَا يُفۡلِحُونَ ٦٩ مَتَٰعٞ فِي ٱلدُّنۡيَا ثُمَّ إِلَيۡنَا مَرۡجِعُهُمۡ ثُمَّ نُذِيقُهُمُ ٱلۡعَذَابَ ٱلشَّدِيدَ بِمَا كَانُواْ يَكۡفُرُونَ ٧٠

67. Shi ne Wanda Ya sanya muku dare don ku samu nutsuwa, rana kuma don haskakawa. Lalle a game da wannan ba tabbas akwai ayoyi ga mutane masu ji.

68. Suke ce Allah Yana da ɗa! Tsarki ya tabbata gare Shi. Shi Mawadaci ne. Abin da yake cikin sammai da abin da yake ƙasa nasa ne. Ko kuna da wata hujja ne game da wannan? Yanzu kwa riƙa faɗar abin da ba ku sani ba game da Allah?

69. Ka ce: "Lalle waɗanda suke ƙaga wa Allah ƙarya ba za su rabauta ba."

70. Jin daɗi ne kawai a cikin duniya, sannan kuma gare Mu ne makomarsu take, sannan Mu ɗanɗana musu azaba mai tsanani saboda abin da suka zamanto suna yi na kafirci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wasu ni'imominsa ne ga ɗan'adam. Ya ambaci cewa shi ne wanda ya halitta musu dare domin su samu hutu a cikinsa bayan sun yi aiki sun gaji, kuma ya samar musu da yini mai haske domin su fita neman abincinsu a cikinsa da biyan buƙatunsu na rayuwa. Lalle game da waɗannan ayyuka na Allah akwai ayoyi masu nuna kaɗaitakarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai ga mutane masu sauraron ayoyin Allah suna ɗaukar izina daga gare su.

Sai kuma ya bayyana cewa, mushirikan Larabawa sun riya cewa wai Allah yana da ɗa, tsarki ya tabbata a gare shi, Allah mawadaci ne ba ya buƙatar mata ko ɗa, kai ba ya da buƙata wajen kowa da komai, sammai da ƙasa duk nasa ne. Don haka ta yaya zai riƙi ɗa daga abin da shi ne ya halicce shi kuma mallakarsa ne? Waɗannan mushirikai masu da'awar cewa Allah yana da ɗa ba su da wata hujja a kan wannan mummunar maganar tasu. To me ya sa za su riƙa maganar da ba su da ilimi a kanta suna jingina ta ga Allah?
Sannan ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tabbatar wa duk masu yi wa Allah ƙarya cewa, ba za su rabauta ba har abada a duniya ko a lahira. A nan duniya za su ji ɗan ji daɗi kaɗan; daga ƙarshe makomarsu zuwa ga Allah ne sannan ya ɗanɗana musu azaba mai raɗaɗi saboda kafircinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karanta tarihin annabawan farko domin ɗaukar darasu daga rayuwarsu.

2. Ya wajaba ga duk mai kira zuwa ga Allah ya cika zuciyarsa da yarda da Allah da dogaro da shi shi kaɗai, domin ya sami kariyarsa daga masu niyyar cutar da shi ko gurgunta da'awarsa.

3. Idan mai kira zuwa ga gaskiya ya riƙi Allah shi kaɗai to in duk duniya za su haɗu domin cutar da shi, ba za su yi nasara ba.

4. Ya wajaba ga mai kira zuwa ga Allah ya yi komai domin Allah, ba don wata buƙata ta duniya ba. Yin hakan shi ne abin da zai taimaka da'awarsa ta samu karɓuwa a wurin mutane.

5. Wa'azin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya damu mutanensa har ya zamanto kamar wani abu mai nauyi yake ƙoƙarin ɗora musu idan ya yi musu wa'azi, saboda daɗewar da ya yi a cikinsu, domin ya zauna a cikinsu shekara dubu ba hamsin.

6. Duk wanda ya daɗe a kan wasu miyagun aƙidu, to zai yi masa nauyi sosai yayin da za a neme shi da ya sauka daga kansu ya riƙe wata sabuwar aƙidar ta daban.

Suratu Yunus (71-73)

*وَٱتۡلُ عَلَيۡهِمۡ نَبَأَ نُوحٍ إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِۦ يَٰقَوۡمِ إِن كَانَ كَبُرَ عَلَيۡكُم مَّقَامِي وَتَذۡكِيرِي بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَعَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلۡتُ فَأَجۡمِعُوٓاْ أَمۡرَكُمۡ وَشُرَكَآءَكُمۡ ثُمَّ لَا يَكُنۡ أَمۡرُكُمۡ عَلَيۡكُمۡ غُمَّةٗ ثُمَّ ٱقۡضُوٓاْ إِلَيَّ وَلَا تُنظِرُونِ ٧١ فَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَمَا سَأَلۡتُكُم مِّنۡ أَجۡرٍۖ إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِۖ وَأُمِرۡتُ أَنۡ أَكُونَ مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ٧٢ فَكَذَّبُوهُ فَنَجَّيۡنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ فِي ٱلۡفُلۡكِ وَجَعَلۡنَٰهُمۡ خَلَٰٓئِفَ وَأَغۡرَقۡنَا ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَاۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُنذَرِينَ ٧٣

71. Ka kuma karanta musu labarin (Annabi) Nuhu, a lokacin da ya ce da mutanensa: "Ya ku mutanena, idan zamana a cikinku da kuma wa'azin da nake muku da ayoyin Allah sun dame ku, to ni fa ga Allah ne kawai na dogara, sai ku tattara al'amarinku ku kuma (ku kira) abokan tarayyarku, sannan kada al'amarin naku ya zama a ɓoye, sannan ku zartar (da shi) a gare ni, kada kuma ku saurara mini.

72. "To idan kuka ba da baya, to ban tambaye ku wani lada ba; ladana yana ga Allah; an kuwa umarce ni da in kasance cikin Musulmai."

73. Sai suka ƙaryata shi, sai Muka tserar da shi da waɗanda suke tare da shi a cikin jirgin ruwa, Muka kuma mayar da su masu maye gurbin (waɗanda suka gabace su), Muka kuma nutsar da waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu. To duba ka ga yadda ƙarshen waɗanda aka yi wa gargaɗi ya kasance.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasu dalilai a kan kaɗaitakarsa da abin da ya gudana tsakanin Manzon Allah (ﷺ) da kafirai, sai kuma ya kawo wasu ƙissoshi na wasu annabawa tare da mutanensu don su zama lallashi ga Annabi (ﷺ) a kan abin da mutanensa suke yi masa na tsangwama da cutarwa.
Allah ya fara da labarin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) inda ya umarci Annabi (ﷺ) da ya karanta wa kafirai labarinsa a lokacin da yake faɗa wa mutanensa cewa, idan zamansa a cikinsu da gargaɗi da yake yi musu da hujjoji masu ƙarfi sun dame su, har suna shirin su auka masa, su cuce shi, to yana shaida musu cewa, shi da Allah kaɗai ya dogara, shi ne wanda zai taimake shi ya kare shi daga sharrinsu. Don haka su gama shirinsu gaba ɗaya na cutar da shi, su ma nemo waɗanda za su taimaka musu, sannan kada su gudanar da al'amarinsu a ɓoye; su zartar da duk abin da suka gama saƙawa a ransu, kada su saurara masa.
Sannan Allah ya bayyana cewa, idan sun bijire wa da'awarsa, to shi fa da man ba yana neman wani lada ne daga wurinsu ba, ladansa yana wurin Allah, shi ne kuma ya umarce shi ya zamanto farkon masu miƙa wuya.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin mutanen Annabi Nuhu cewa, sun ƙaryata shi, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da shi da waɗanda suka yi imani da shi a cikin jirgin ruwa, su kuma waɗanda suka kafirce masa, Allah ya nutsar da su a cikin ruwan Ɗufana.

Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi tunani da duba na tsanaki game da yadda ƙarshen al'amarin mutanen da manzonsu ya yi musu gargaɗin azabar Allah ya kasance.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Munin tsafi da bayanin mugun ƙarshen matsafa.

2. Bin addinin gargajiya shi ne yake hana yawancin al 'ummu karɓar kiran manzanni.

3. Wasu sukan ƙi gaskiya ne domin a zatonsu mai kiran su zuwa gaskiya yana neman girma ne kawai, don haka su ba za su miƙa masa wuya ba.

Suratu Yunus (74-78)

ثُمَّ بَعَثۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِۦ رُسُلًا إِلَىٰ قَوۡمِهِمۡ فَجَآءُوهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَمَا كَانُواْ لِيُؤۡمِنُواْ بِمَا كَذَّبُواْ بِهِۦ مِن قَبۡلُۚ كَذَٰلِكَ نَطۡبَعُ عَلَىٰ قُلُوبِ ٱلۡمُعۡتَدِينَ ٧٤ ثُمَّ بَعَثۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِم مُّوسَىٰ وَهَٰرُونَ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَإِيْهِۦ بِـَٔايَٰتِنَا فَٱسۡتَكۡبَرُواْ وَكَانُواْ قَوۡمٗا مُّجۡرِمِينَ ٧٥ فَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ مِنۡ عِندِنَا قَالُوٓاْ إِنَّ هَٰذَا لَسِحۡرٞ مُّبِينٞ ٧٦ قَالَ مُوسَىٰٓ أَتَقُولُونَ لِلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَكُمۡۖ أَسِحۡرٌ هَٰذَا وَلَا يُفۡلِحُ ٱلسَّٰحِرُونَ ٧٧ قَالُوٓاْ أَجِئۡتَنَا لِتَلۡفِتَنَا عَمَّا وَجَدۡنَا عَلَيۡهِ ءَابَآءَنَا وَتَكُونَ لَكُمَا ٱلۡكِبۡرِيَآءُ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا نَحۡنُ لَكُمَا بِمُؤۡمِنِينَ ٧٨

74. Sannan a bayansa (Annabi Nuhu) Muka aika manzanni zuwa ga mutanensu suka zo musu da (ayoyi) mabayyana, ba su zamanto suna gaskata abin da a da can suke ƙaryata shi ba. Kamar haka ne Muke tushe zukatan masu shisshigi.

75. Sannan daga bayansu Muka aiko Musa da Haruna zuwa ga Fir'auna shi da jama'arsa da ayoyinmu, sai suka yi girman kai suka kuwa zamanto mutane masu laifi.

76. To lokacin da gaskiya ta zo musu daga wurinmu sai suka ce: "Lalle wannan tabbas tsafi ne bayyananne."

77. Musa ya ce: "Yanzu kwa riƙa ce wa gaskiya (tsafi) lokacin da ta zo muku? Yanzu wannan ne tsafin, alhali kuwa matsafa ba sa cin nasara?" 78. Suka ce: "Yanzu ka zo mana ne don ka raba mu da abin da muka sami iyayenmu a kansa, ku kuma (kai da Haruna) ku zamanto ku ne masu girma a bayan ƙasa? Mu kam ba za mu yi imani da ku ba!"

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin ya aiko da wasu manzannin bayan wucewar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya ba su mu'ijizoji masu tabbatar da ingancin manzancinsu ga mutanensu, to amma sai waɗanda suka rungumi kafirci daga cikin mutanensu suka ƙi yarda su ba da gaskiya da su, to Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rufe zukatansu domin sun ƙi yin imani. To kamar haka ne Allah yake rufe zukatan masu shisshigi.Bayan wucewar waɗannan manzanni Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko da Annabi Musa da Haruna zuwa ga Fir'auna da jama'arsa, ya ba su mu'ujizoji masu tabbatar da gaskiyarsu, to amma sai mutanen Fir'auna suka yi girman kai suka ƙi karɓar gaskiya suka kuma zamanto mutane masu laifi.Yayin da Annabi Musa ya zo wa Fir'auna da saƙo na gaskiya

sai shi da mutanensa suka bijire suka ce wai abin da Musa ya zo da shi tsafi ne bayyananne. Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tsawatar musu da cewa, yanzu gaskiyar da ta zo musu suke gani da idanunsu ita ce za su kira tsafi? Matsafa ai ba sa rabauta a duniya da lahira.
Jin wannan ya sa Fir'auna da manyan fadawansa suka tambayi Annabi Musa cewa, yanzu ya zo ne don ya raba su da bautar abin da suka sami iyayensu suna bauta wa, su kuma Annabi Musa da Haruna girma da sarauta su zama nasu? To su kam ba za su yi imani da su ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Musa ya umarci matsafa da su fara jefar da igiyoyinsu da sandunansu domin daga bisani ya jefa tasa sandar ta yi rinjaye a kan nasu domin hujjarsa da gaskiyarsa ta bayyana ga kowa.

2. Tsafi gaskiya ne akwai shi a aikace, sai dai aikata shi kafirce ne.

3. Duk wani maɓarnaci da zai zo da wata ɓarna ko wani makirci, to ɓarnarsa da makircinsa za su gushe wata rana, ko da kuwa ya ci kasuwa a wurin wasu, wannan na ɗan lokaci ne. Saɓanin mutanen kirki su kam ayyukansu masu ɗorewa ne domin Allah ne mai tallafa musu game da ayyukansu na ƙwarai.

Suratu Yunus (79-82)

وَقَالَ فِرۡعَوۡنُ ٱئۡتُونِي بِكُلِّ سَٰحِرٍ عَلِيمٖ ٧٩ فَلَمَّا جَآءَ ٱلسَّحَرَةُ قَالَ لَهُم مُّوسَىٰٓ أَلۡقُواْ مَآ أَنتُم مُّلۡقُونَ ٨٠ فَلَمَّآ أَلۡقَوۡاْ قَالَ مُوسَىٰ مَا جِئۡتُم بِهِ ٱلسِّحۡرُۖ إِنَّ ٱللَّهَ سَيُبۡطِلُهُۥٓۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُصۡلِحُ عَمَلَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ٨١ وَيُحِقُّ ٱللَّهُ ٱلۡحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٨٢

79. Fir'auna kuma ya ce: "Ku zo mini da duk wani ƙwararren matsafi."

80. To lokacin da matsafan suka zo, sai Musa ya ce da su: "Ku jefa duk abin da za ku jefa."

81. To lokacin da suka jefa (kayan tsafinsu), sai Musa ya ce: "Ai abin da kuka zo da shi tsafi ne; lalle ko Allah zai ɓata shi. Lalle Allah ba Ya gyara aikin maɓarnata.

82. "Allah zai tabbatar da gaskiya da ikonsa ko da kuwa masu manyan laifuka sun ƙi."

Lokacin da Fir'auna da fadawansa suka zargi Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa shi matsafi ne, sai kuma suka shiga laluben abin da za su kafa hujja da shi a kan wannan zargin nasu. Allah ya ba da labarin cewa yayin da Fir'auna da mutanensa suka ga dagewar Annabi Musa a kan da'awarsa zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, sai Fir'auna ya yi shela da a gayyato masa duk wani gwanin tsafi daga ko'ina a ƙasar. Yayin da suka hallara, sai Annabi Musa ya umarce da su jefar da igiyoyinsu da sandunansu a ƙasa; da suka jefar sai igiyoyin da sandunan suka rikɗa gudu a ƙasa, sai Annabi Musa ya ce, wannan abu da suka kawo shi ne tsafi, kuma Allah zai rushe shi, kuma Allah ba ya gyara aikin maɓarnata, kuma shi zai tabbatar da gaskiyar da Annabi Musa ya zo da ita ko da kuwa masu laifi sun ƙi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin Manzon Allah (ﷺ) a kan ƙarancin waɗanda suka yi imani da shi, saboda Annabi Musa ma (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) haka ne ya faru da shi duk kuwa da bayyanar hujjojinsa a fili.

2. Matasa sau tari sun fi saurin karɓar gaskiya fiye da masu yawan shekaru, saboda ba su yi nisa cikin ɓata ba kamar yadda iyayensu suka yi.

3. Imani wani sinadari ne na ƙarin ƙarfi ga waɗanda suke ‘yan tsiraru wajen fuskantar barazanar manyan maɓarnata da azzalumai a bayan ƙasa.

4. Yana da kyau mai addu’a ya dogara ga Allah shi kaɗai, wannan shi zai sa addu’arsa ta sami karɓuwa.

Suratu Yunus (83-86)

فَمَآ ءَامَنَ لِمُوسَىٰٓ إِلَّا ذُرِّيَّةٌ مِّن قَوْمِهِۦ عَلَىٰ خَوْفٍ مِّن فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِمْ أَن يَفْتِنَهُمْۚ وَإِنَّ فِرْعَوْنَ لَعَالٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَإِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلْمُسْرِفِينَ﴿٨٣﴾ وَقَالَ مُوسَىٰ يَٰقَوْمِ إِن كُنتُمْ ءَامَنتُم بِٱللَّهِ فَعَلَيْهِ تَوَكَّلُوٓاْ إِن كُنتُم مُّسْلِمِينَ﴿٨٤﴾ فَقَالُواْ عَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلْنَا رَبَّنَا لَا تَجْعَلْنَا فِتْنَةً لِّلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ﴿٨٥﴾ وَنَجِّنَا بِرَحْمَتِكَ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ﴿٨٦﴾

83. To ba wanda ya yi imani da Musa sai wasu ‘yan samari daga mutanensa don tsoron kada Fir’auna da mutanensa su azabtar da su. Kuma lalle Fir’auna ya tabbata mai girman kai ne a bayan ƙasa. Lalle kuma shi yana cikin maɓarnata.

84. Musa kuma ya ce: “Ya ku mutanena, idan har kun yi imani da Allah, to a gare Shi kawai za ku dogara in kun kasance Musulmai.

85. Sai suka ce: “Ga Allah kaɗai muka dogara. Ya Ubangijinmu, kada ka sanya mu zama fitina ga mutane azzalumai.

86. ‘‘Ka kuma tserar da mu da rahamarka daga mutane kafirai.’’

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, duk da irin ƙarfafan hujjoji da Annabi Musa ya nuna wa mutanensa, babu wanda ya yi imani da shi sai wasu samari kaɗan daga cikin mutanen Fir’auna saboda tsoron fitinarsa da ta mutanensa. Kuma lalle Fir’auna babban mai girman kai ne da zalunci a bayan ƙasa, sannan kuma ya yi nisa sosai cikin kafirci da ɓarna.
Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi ta lallashin mutanensa waɗanda suka yi imani da shi yana kwantar musu da hankali da cewa, su dogara ga Allah shi kaɗai su miƙa wuya gare shi matuƙar dai sun kasance Musulmi. Jin haka Banu Isra’ila suka ce sun dogara ga Allah shi kaɗai, kuma suka roƙe shi da kada ya sanya su zama fitina ga kafirai, watau kada ya ba kafirai nasara a kansu har su riƙa zaton ko su ne a kan gaskiya, muminai kuma a kan ƙarya. Suka kuma roƙe shi da ya tserar da su da rahamarsa daga mutane kafirai, watau Fir’auna da jama’arsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samuwar dukiya ko mulki a hannun waɗanda ba sa tsoron Allah wani babban haɗari ne ga masu raunin imani, domin za a yi amfani da wannan dukiya ko mulki wajen ɓatar da su daga kan gaskiya.

2. Yayin da zaluncin mutum ya tsananta ga bayin Allah, ya halatta a roƙi Allah ya yi wa muminai maganinsa bayan an cire tsammanin shiryuwarsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana toshe zuciyar wanda ya cancanta ya toshe zuciyarsa, ya hana imani shiga cikinta, saboda yawan kafircinsa da saɓon Allah.

4. Amsa addu'ar Annabi Musa da ɗan'uwansa Haruna a kan Fir'auna dalili ne a kan cewa Fir'auna ya mutu kafiri.

5. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne mai addu'a, Annabi Haruna kuwa yana cewa: Amin. Dukansu Allah ya jingina musu addu'ar, wannan yana nuna mai cewa 'amin' yayin addu'a shi ma mai yin addu'a ne.

Suratu Yunus (87-89)

وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰ وَأَخِيهِ أَن تَبَوَّءَا لِقَوۡمِكُمَا بِمِصۡرَ بُيُوتٗا وَٱجۡعَلُواْ بُيُوتَكُمۡ قِبۡلَةٗ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٨٧ وَقَالَ مُوسَىٰ رَبَّنَآ إِنَّكَ ءَاتَيۡتَ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَأَهُۥ زِينَةٗ وَأَمۡوَٰلٗا فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا رَبَّنَا لِيُضِلُّواْ عَن سَبِيلِكَۖ رَبَّنَا ٱطۡمِسۡ عَلَىٰٓ أَمۡوَٰلِهِمۡ وَٱشۡدُدۡ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ فَلَا يُؤۡمِنُواْ حَتَّىٰ يَرَوُاْ ٱلۡعَذَابَ ٱلۡأَلِيمَ ٨٨ قَالَ قَدۡ أُجِيبَت دَّعۡوَتُكُمَا فَٱسۡتَقِيمَا وَلَا تَتَّبِعَآنِّ سَبِيلَ ٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَ ٨٩

87. Kuma Muka yi wa Musa wahayi shi da ɗan'uwansa cewa: "Ku tanadar wa mutanenku gidaje a Masar, ku kuma sanya gidajenku wurin salla." Ka kuma yi wa muminai albishir (da samun nasara).

88. Musa kuma ya ce: "Ya Ubangijinmu, lalle Ka bai wa Fir'auna da mutanensa kayan ado da kuma dukiyoyi a rayuwar duniya; ya Ubangijimu, don su ɓatar (da jama'a) daga hanyarka; ya Ubangijimu, Ka shafe dukiyoyinsu Ka kuma ƙeƙasar da zukatansu ba za su yi imani ba har sai sun ga azaba mai raɗaɗi."

89. (Allah) Ya ce: "Haƙiƙa an amsa addu'arku, sai ku tsaya ƙyam (a kan tafarkinku), kada kuwa ku bi hanyar waɗanda ba sa sanin (gaskiya)."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa ya yi wa Annabi Musa da ɗan'uwansa Haruna wahayi cewa, su tanadar wa mutanensu gidajen zama a garin Masar, sannan su mayar da su wuraren sallolinsu, su kuma yi sallolinsu na farilla a kan lokaci, kuma ya ya umarci Annabi Musa da ya yi wa muminai albishir da samun nasara da lada daga Allah.
Sai kuma Annabi Musa ya yi addu'a ga Fir'auna da azzaluman mutanensa yana mai faɗa wa Allah cewa, ga shi dai ya ba wa Fir'auna da manyan fadawansa kayan ado na more rayuwar duniya da dukiya mai yawa domin ta zama fitina a gare su, su yi amfani da ita don su ɓatar da mutane, hakan kuma ya zame musu uƙuba gare su. Don haka ya roƙe shi da ya lalata dukiyoyinsu ta yadda ba za su more su ba, sannan ya doƙe musu zukatansu don kuwa ya tabbata cewa ba za su yi imani ba har sai sun ga azaba mai raɗaɗî ta afka musu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Musa da Haruna cewa, ya amsa musu addu'arsu, don haka su ci gaba da tsayawa ƙyam a kan addininsu, su ci gaba da da'awarsu da wa'azinsu ga Fir'auna da mutanensa, kada su bi hanyar waɗanda ba su san komai dangane da gaskiyar alƙawarinsa ba, da kuma cewar shi ba ya saɓa alƙawarinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani ba ya da amfani bayan mutuwa ta riga ta zo wa mutum, ko ya ga azabar Allah gadan-gadan ta sauko masa.

2. Faɗar Allah cewa: "….har sai da nutsewa ta riske shi sai ya ce: 'Na yi imani….'" tana nuna cewa, Fir'auna ya yi ta ƙoƙarin ya kuɓuce wa halaka ya fice daga ruwa, amma hakan bai samu ba har mutuwa ta cim masa, to a lokacin ne ya saduda ya furta imaninsa ga Allah.

3. Faɗin Allah ga Fir'auna: "Sai yanzu kuma, bayan da can ka yi ta saɓo….", shi ma yana nuna cewa, Fir'auna ya mutu kafiri, domin a nan zargin sa ne Allah yake yi da sukan lamirinsa. Da a ce an karɓi imaninsa a lokacin, da ba za a faɗa masa haka ba. Hakanan fito da gawarsa daga cikin ruwa kowa ya gani alama ce ta ƙaskantarwa da wulaƙantarwa gare shi. Da a ce an karɓi imaninsa da hakan bai faru gare shi ba.

Suratu Yunus (90-92)

*وَجَٰوَزۡنَا بِبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱلۡبَحۡرَ فَأَتۡبَعَهُمۡ فِرۡعَوۡنُ وَجُنُودُهُۥ بَغۡيٗا وَعَدۡوًاۖ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَدۡرَكَهُ ٱلۡغَرَقُ قَالَ ءَامَنتُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱلَّذِيٓ ءَامَنَتۡ بِهِۦ بَنُوٓاْ إِسۡرَٰٓءِيلَ وَأَنَا۠ مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ٩٠ ءَآلۡـَٰٔنَ وَقَدۡ عَصَيۡتَ قَبۡلُ وَكُنتَ مِنَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ٩١ فَٱلۡيَوۡمَ نُنَجِّيكَ بِبَدَنِكَ لِتَكُونَ لِمَنۡ خَلۡفَكَ ءَايَةٗۚ وَإِنَّ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلنَّاسِ عَنۡ ءَايَٰتِنَا لَغَٰفِلُونَ ٩٢

90. Muka kuma ƙetarar da Banu Isra'ila kogi, sai Fir'auna ya bi su shi da rundunarsa don zalunci da ta'addanci, har sai lokacin da nutsewa ta riske shi sai ya ce: "Na yi imani cewa babu wani abin bauta sai wanda Banu Isra'ila suka yi imani da shi, kuma ni ina cikin Musulmai."

91. Sai yanzu kuma, bayan da can ka yi ta saɓo, ka kuma kasance cikin masu ɓarna?

92. To a yau kam za Mu tserar da gangar jikinka don ka zamanto aya ga na bayanka. Lalle kuwa yawancin mutane masu gafala ne ga lura da ayoyinmu.

A nan Allah yana bayanin cewa ya ƙetarar da Banu Isra'ila kogi. Fir'auna kuma da rundunarsa ta zalunci suka bi su da niyyar dawo da su ga azaba da wulaƙanci, to amma sai ruwa ya haɗiye su. Lokacin da Fir'auna ya ga halaka ne, ruwa zai ci shi, sannan ne ya ce ya yi imani babu wani abin bauta sai wanda Banu Isra'ila suka yi imani da shi kuma yana cikin masu miƙa wuya, watau dai zai yi biyayya ga Annabi Musa da abin da ya zo da shi na gaskiya. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar masa da martani cewa, sai yanzu ne zai ce ya yi imani, alhalin a baya kafin ya ga wannan halaka ya saɓa masa ya tabbata cikin maɓarnata masu hana a bi gaskiya? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa cewa, to a wannan lokaci zai fito da gawarsa fili a kan tudu domin duk wanda zai ƙaryata halakarsa ya ga gawarsa da idonsa, kuma ya zama darasi ga 'yan bayansa, domin yawancin mutane gafalallu ne ga lura da ayoyin Allah ba sa ɗaukar izina.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan Shaiɗan ya kasa cin nasara a kan bayin Allah na ƙwarai, to sai ya yi ƙoƙarin saka su cikin saɓani da rarrabuwar kai da ƙiyayyar juna.

2. Yawaita kawo dalilai da hujjojin gaskiyar Annabi (ﷺ) domin ƙarin samun yaƙini da nutsuwa a zuciya game da abin da ya zo da shi na Tauhidi.

3. Kafa wa Yahudu da Nasara hujja da iliminsu wanda suka yarda da shi.

4. Faɗakarwa ga duk wanda ya samu wata tababa game da wani abu na addini a kan ya gaggauta komawa ga malamai masana shari'a su yi masa bayanin da zai kawar masa da wannan tababar daga zuciyarsa.

وَلَقَدۡ بَوَّأۡنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ مُبَوَّأَ صِدۡقٖ وَرَزَقۡنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ فَمَا ٱخۡتَلَفُواْ حَتَّىٰ جَآءَهُمُ ٱلۡعِلۡمُۚ إِنَّ رَبَّكَ يَقۡضِي بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ٩٣ فَإِن كُنتَ فِي شَكّٖ مِّمَّآ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ فَسۡـَٔلِ ٱلَّذِينَ يَقۡرَءُونَ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِكَۚ لَقَدۡ جَآءَكَ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡمُمۡتَرِينَ ٩٤ وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَتَكُونَ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٩٥

93. Haƙiƙa Mun sanya Banu Isra'ila a kyakkyawan matsayi na gaskiya, Muka kuma arzuta su da abubuwa daɗaɗa na halal, to kawunansu ba su tashi rabuwa ba har sai lokacin da ilimi ya zo musu. Lalle Ubangijinka zai yi hukunci tsakaninsu ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna saɓani a kansa.

94. To idan kana tababa game da abin da Muka saukar maka to sai ka tambayi waɗanda suke karanta littafi gabaninka. Haƙiƙa gaskiya ta zo maka daga Ubangijinka; to kada ka zama daga cikin masu kokwanto.

95. Lalle kuma kada ka kasance daga cikin waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah, sai ka zamo daga asararru.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana irin ni'imomin da ya yi wa Banu Isra'ila, ya saukar da su kyawawan gidaje masu nagarta, ya kuma arzuta su da daɗaɗan abubuwa na halal na ƙasa mai albarka. Ba su yi saɓani a kan gaskiyar aiko Manzon Allah (ﷺ) ba har sai da Alƙur'ani ya sauko da bayanin gaskiyar manzancinsa da addininsa, a lokacin ne yawancinsu suka ƙaryata. Ya bayyana wa Manzon Allah (ﷺ) cewa Ubangijinsa zai yi musu hukunci a ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna saɓani a kansa na al'amarin manzancinsa, sai ya shigar da masu ƙaryatawa gidan wuta, ya shigar da muminai Aljanna.
Sai kuma ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa idan yana tababa game da abin da Allah ya saukar masa, to ya tambayi waɗanda suke karanta littafin da Allah ya saukar gabanin Alƙur'ani, watau Attaura da Linjila, wannan batun da yake faɗa masa yana nan tabbace a cikin littattafansu.

A nan babu abin da ya nuna Annabi (ﷺ) ya yi tababa ko shakka game da wahayi da Allah ya yi masa, sai dai ana nufin ne a tsayar wa da ma'abota littafi hujjar gaskiyar annabcin Manzon Allah (ﷺ), a nuna musu cewa hakan yana nan a rubuce a cikin littattafansu a wurin malamansu, idan aka tambaye su, in za su faɗi gaskiya, to za su bayyana hakan. Hakanan waɗanda suka yi imani daga cikin ma'abota littafi, kamar Abdullahi ɗan Salam da jama'arsa, sun tabbatar da hakan.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi Annabi (ﷺ) da kada ya zamanto daga cikin masu shakka, kuma kada ya zamanto cikin waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah sai ya zamo cikin hasararru waɗanda Allah ya yi fushi da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ƙarfin hujja shi kaɗai ba zai shiryar da bawa ya fahimci gaskiya ba sai da taimakon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da shiryarwarsa.

2. Allah ya karɓi tuban mutanen Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan ya gargaɗe su da idan ba su tuba ba, to azaba na nan tafe mai halakar da su. Lokacin da suka fara ganin ɓurɓushin alamun zuwanta sai suka yi maza suka tuba kafin ta ƙaraso gare su, sai kuma Allah ya karɓi tubansu. Saɓanin Fir'auna wanda Allah ya ƙi karɓar tubansa, ya hukunta masa kafirci da shiga wuta har abada, domin shi bai tuba ba har sai da azaba ta cim masa, halakar ta gama tabbata a kansa, a wannan lokaci ne ya nuna nadamarsa da imaninsa Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙi karɓar irin wannan tuba nasa.

Suratu Yunus (96-100)

إِنَّ ٱلَّذِينَ حَقَّتۡ عَلَيۡهِمۡ كَلِمَتُ رَبِّكَ لَا يُؤۡمِنُونَ ٩٦ وَلَوۡ جَآءَتۡهُمۡ كُلُّ ءَايَةٍ حَتَّىٰ يَرَوُاْ ٱلۡعَذَابَ ٱلۡأَلِيمَ ٩٧ فَلَوۡلَا كَانَتۡ قَرۡيَةٌ ءَامَنَتۡ فَنَفَعَهَآ إِيمَٰنُهَآ إِلَّا قَوۡمَ يُونُسَ لَمَّآ ءَامَنُواْ كَشَفۡنَا عَنۡهُمۡ عَذَابَ ٱلۡخِزۡيِ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَمَتَّعۡنَٰهُمۡ إِلَىٰ حِينٖ ٩٨ وَلَوۡ شَآءَ رَبُّكَ لَأٓمَنَ مَن فِي ٱلۡأَرۡضِ كُلُّهُمۡ جَمِيعًاۚ أَفَأَنتَ تُكۡرِهُ ٱلنَّاسَ حَتَّىٰ يَكُونُواْ مُؤۡمِنِينَ ٩٩ وَمَا كَانَ لِنَفۡسٍ أَن تُؤۡمِنَ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ وَيَجۡعَلُ ٱلرِّجۡسَ عَلَى ٱلَّذِينَ لَا يَعۡقِلُونَ ١٠٠

96. Lalle waɗanda kalmar Ubangijinka ta tabbata a kansu (ta zamansu ‘yan wuta) ba za su yi imani ba.

97. Ko da kuwa dukkanin ayoyi sun zo musu har sai sun ga azaba mai raɗaɗî.

98. Babu wasu mutane na wata alƙarya da suka yi imani, sannan imaninsu ya amfane su, sai fa mutanen Yunusa, lokacin da suka yi imani sai Muka yaye musu azabar wulaƙanci a rayuwar duniya, Muka kuma jiyar da su daɗî har zuwa wani lokaci (iyakantacce).

99. Da Ubangijinka Ya ga dama lalle da duk waɗanda suke bayan ƙasa sun yi imani gaba ɗayansu. Shin kai ne za ka tilasa wa mutane har su zama muminai?

100. Ba zai yiwu wani rai ya yi imani ba sai da izinin Allah. Yana kuma sanya azaba ne a kan waɗanda ba sa hankalta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, waɗanda kalmar Allah ta tabbata a kansu cewa za su mutu a kan kafirci, ba za su rabauta da rahamar Allah ba, don haka waɗannan ba za su taɓa yin imanin da zai yi musu amfani ba kafin mutuwarsu, ko da kuwa dukkan wasu ayoyi da hujjoji sun zo musu, har sai sun ga azaba mai raɗaɗî ƙarara ta zo musu, to a lokacin ne za su ce sun yi imani, imanin da ba zai yi musu amfani ba.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin mutanen alƙaryar Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka yi imani bayan sun tabbatar da azaba za ta zo musu a halaka su gaba ɗaya, sai kuma imaninsu ya amfane su, Allah ya tserar da su ya janye musu azabar. Allah ya bayyana cewa, babu wata alƙarya da ya taɓa halakar wa a baya da aka yi musu irin wannan alfarmar sai mutanen Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya bar su suka ci gaba da more rayuwarsu har zuwa lokutan mutuwarsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, da ya ga dama da waɗanda suke a doron ƙasa sun yi imani gaba ɗayansu da abin da ya zo musu da shi, sai dai Allah yana da hikimarsa a nan, yana shiryar da wanda ya ga dama, ya ɓatar da wanda ya ga dama bisa hikimarsa, don haka shi Manzon Allah (ﷺ) ba zai iya tilasta wa mutane sai sun yi imani ba. Kuma ma babu wani rai da zai yi imani sai da ganin damar Allah da ƙaddarawarsa, don haka kada Manzon Allah ya wahalar da kansa a kan wannan, domin al’amarinsu duka yana hannun Allah ne, don haka yana sanya fushinsa da azabarsa a kan mutanen da ba sa hankaltar umarninsa da haninsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah yana kiran bayinsa zuwa ga duba cikin halittun da ya ajiye a sama da ƙasa don ɗaukar darasi da izina da dalilai masu jagoranci zuwa ga sanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Wanda Allah bai nufe shi da shiriya ba, yawan hujjoji da dalilai masu ƙarfi ba za su sa ya shiriya ba.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta wa kansa taimakon masu imani da tserar da su daga duk wata musiba da sharaɗin su inganta imaninsu da shi.

Suratu Yunus (101-103)

قُلِ ٱنظُرُواْ مَاذَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَمَا تُغۡنِي ٱلۡأٓيَٰتُ وَٱلنُّذُرُ عَن قَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ ١٠١ فَهَلۡ يَنتَظِرُونَ إِلَّا مِثۡلَ أَيَّامِ ٱلَّذِينَ خَلَوۡاْ مِن قَبۡلِهِمۡۚ قُلۡ فَٱنتَظِرُوٓاْ إِنِّي مَعَكُم مِّنَ ٱلۡمُنتَظِرِينَ ١٠٢ ثُمَّ نُنَجِّي رُسُلَنَا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْۚ كَذَٰلِكَ حَقًّا عَلَيۡنَا نُنجِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٠٣

101. Ka ce: “Ku yi tunanin abubuwan da suke cikin sammai da ƙasa.” Ayoyi kuwa da masu gargaɗi ba sa wadatar da mutanen da ba sa yin imani.

102. Ai ba abin da suke saurare sai irin azabar da ta sami waɗanda suka wuce gabaninsu. Ka ce: “Sai ku saurara, lalle ni ma ina tare da ku cikin masu sauraro.”

103. Sannan Muka riƙa tserar da manzanninmu da waɗanda suka yi imani da su. Kamar haka ne ya zama lalle a kanmu Mu tserar da muminai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa mushirikai masu neman wasu mu’ujizoji daga gare shi cewa, su yi duba da tunani game da abin da yake cikin sammai da ƙasa na ayoyin Allah bayyanannu, su kaɗai sun ishe su ba sai sun nemi wasu ayoyi daban ba. Ayoyin Allah da wa’azuzzuka da manzanni masu gargaɗin bayi game da azabar Allah ba za su amfani mutanen da ba su yi imani da su ba, saboda tsaurin kansu da bijirewarsu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara da cewa, to yanzu shin waɗannan mutane akwai abin da suke jira ne in ban da irin abin da ya sami kafiran da suka gabace su na azabar Allah ya same su?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi ya faɗa musu cewa, su jira lokacin zuwan azabar Allah gare su, shi ma yana tare da su yana jiran hakan. Idan kuma azabar ta zo to Allah yakan tserar da manzanninsa da waɗanda suka yi imani tare da su, to haka shi ma Manzon Allah (ﷺ), Allah zai kuɓutar da shi da waɗanda suka yi imani da shi da rahamarsa da falalarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cikin kafiran Ƙuraishawa akwai waɗanda suka shiga tababa bayan sun ga dalilan gaskiyar Annabi (ﷺ), suka fara shakkar al’amarinsu.

2. Duk tsananin kafircin mushirikai ba su taɓa da’awar cewa gumakansu suna kashewa da rayawa ba, sun yarda Allah ne kaɗai yake aikata hakan.

3. Gargaɗi mai tsanani a kan aikata shirka.

4. Babu mai saukar da wata cuta ko kuma ya yaye ta sai Allah shi kaɗai, don haka neman yayewar wata cuta daga wani ba Allah ba shirka ne da Allah.

5. Duk wanda Allah ya nufe shi da alheri to babu wanda ya isa ya hana, don haka wajibi ne mutum ya nemi biyan buƙatarsa daga wajen Allah shi kaɗai.

6. Duk wanda ya shiriya, to don amfanin kansa ne, Allah mawadaci ne ba ya buƙatar komai daga halittarsa. Hakanan duk wanda ya ɓace to kansa ya cuta, bai cuci Allah da komai ba.

7. Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) an umarce shi da bin abin da aka yi masa wahayinsa, ba shi da damar ƙara wani abu a addinin Allah wanda Allah bai yi izini a kansa ba.

Suratu Yunus (104-109)

قُلْ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِن كُنتُمْ فِى شَكٍّ مِّن دِينِى فَلَآ أَعْبُدُ ٱلَّذِينَ تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَـٰكِنْ أَعْبُدُ ٱللَّهَ ٱلَّذِى يَتَوَفَّىٰكُمْ ۖ وَأُمِرْتُ أَنْ أَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٠٤﴾ وَأَنْ أَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًا وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٠٥﴾ وَلَا تَدْعُ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكَ وَلَا يَضُرُّكَ ۖ فَإِن فَعَلْتَ فَإِنَّكَ إِذًا مِّنَ ٱلظَّـٰلِمِينَ ﴿١٠٦﴾ وَإِن يَمْسَسْكَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَ ۖ وَإِن يُرِدْكَ بِخَيْرٍ فَلَا رَآدَّ لِفَضْلِهِۦ ۚ يُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ ۚ وَهُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٠٧﴾ قُلْ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدْ جَآءَكُمُ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكُمْ ۖ فَمَنِ ٱهْتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهْتَدِى لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيْهَا ۖ وَمَآ أَنَا۠ عَلَيْكُم بِوَكِيلٍ ﴿١٠٨﴾ وَٱتَّبِعْ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيْكَ وَٱصْبِرْ حَتَّىٰ يَحْكُمَ ٱللَّهُ ۚ وَهُوَ خَيْرُ ٱلْحَـٰكِمِينَ ﴿١٠٩﴾

104. Ka ce: “Ya ku mutane, idan kun kasance cikin kokwanto game da addinina, to ba zan bauta wa waɗanda kuke bauta wa ba Allah ba, sai dai ni zan bauta wa Allah ne wanda Yake karɓar rayukanku, an kuma umarce ni da in zama cikin muminai.

105. “Kuma (an umarce ni) da cewa: ‘Ka tsai da fuskarka ga addinin Allah wanda ya karkace wa ɓarna, kada kuma ka kasance cikin mushirikai.

106. “Kada kuma ka bauta wa wani ba Allah ba, abin da ba zai amfane ka ba, ba kuma zai cuce ka ba; to idan kuwa ka aikata haka to lalle daga sannan ka zama cikin azzalumai.’”

107. Idan Allah Ya ɗora maka wata cuta to ba mai yaye maka ita sai shi; idan kuma Ya nufe ka da alheri to ba mai juyar da falalarsa. Yana bayar da shi ga waɗanda Ya ga dama daga bayinsa. Shi ne kuma Mai gafara, Mai jin ƙai.

108. Ka ce: “Ya ku mutane, haƙiƙa gaskiya ta zo muku daga Ubangijinku; duk wanda ya shiriya to ya shiriya ne don kansa; wanda kuma ya ɓace to lalle ya ɓace don kansa ne; ni kuwa ba wakili ne a kanku ba.”

109. Kuma ka bi abin da aka yi maka wahayinsa, ka kuma yi haƙuri har sai Allah Ya yi hukunci. Shi ne kuwa Fiyayyen masu hukunci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) ya faɗa wa mushirikai cewa, idan su suna shakkar addinin da ya kawo musu, watau Musulunci, to shi fa ba zai taɓa amincewa ya bauta wa gumakansu da suke bauta wa ba; shi Allah kaɗai yake bauta wa, shi ne kuma mai karɓar rayukansu idan lokacin mutuwarsu ya zo; ya kuma shaida musu Allah ya umarce shi ya kasance daga muminai. Kuma ya sanar da su cewa, Allah ya umarce shi da ya tsaya ƙyam a kan addinin Musulunci ya kauce wa duk wata ɓarna, kada kuma ya kuskura ya zama cikin masu haɗa Allah da wasu kishiyoyi cikin bauta. Idan kuwa har ya yi hakan, to zai zama cikin halakakku. Kuma Allah ya hane shi da bauta wa duk wani abu da ba zai amfane shi da komai ba, ba kuma zai cutar da shi da komai ba, idan kuwa har ya yi haka, to ya tabbata cikin azzalumai masu shirka.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ƙarfafa masa cewa, idan Allah ya nufe shi da samun wata cuta ko wani balaʾi, to babu mai yaye masa su sai Allah, idan kuwa ya nufe shi da wani alhairi ko wata niʾima, to babu wanda ya isa ya hana masa samun su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne yake nufin bayinsa da samun abin da ya ga dama mai daɗi ko marar daɗi, shi ne kuma yake gafarta wa wanda ya tuba daga zunubansa, yake jin ƙan wanda ya yi imani da shi ya yi masa ɗaʾa.

Haka kuma ya umarce shi da ya faɗa wa mutane cewa, Alƙurʾani da ya zo musu da shi cike yake da shiriya da gaskiya daga Ubangijinsu mahalicci, don haka wanda ya karɓi shiriyarsa to kansa ya yi wa kyakkyawan tanadi, wanda kuwa ya bijire masa, ya doge a kan ɓata, to shi ma wannan kansa kaɗai ya cuta. Annabi (ﷺ) ba mai gadin kowa ne ba, da zai tsaya a kan mutum dole sai ya yi imani; shi ma yana bin umarni na wahayin da aka yi masa ne daga Allah; an kuma umarce shi da ya yi aiki da shi sau-da-ƙafa, ya kuma yi haƙuri a kan biyayyar Allah da jurewa a kan masu cutar da shi, har ya samu ya isar da saƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), a ƙarshe kuma Allah zai yi hukunci a tsakaninsa da su, domin shi ne Fiyayyen masu hukunci, kuma hukuncinsa cike yake da adalci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙurʾani littafi ne mai cike da hikima da fasaha da bayanai dalla-dalla.

2. Babban aikin manzannin Allah shi ne bayani a kan kaɗaita Allah da bauta da kauce wa yi masa shirka.

3. Yawan istigfari da tuba zuwa ga Allah yana kawo kyakkyawar rayuwar duniya ga bawa da cikakken sakamako a lahira.

4. Wajabcin bin Alƙurʾani da sunnar Annabi (ﷺ) a koyaushe.

5. Wajibi ne bawa mumini ya riƙa halarto wa zuciyarsa cewa, Allah yana ganin sa kuma ya san komai yake ciki a koʾina kuma a koyaushe.

11-Suratu Hud

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
'Suratu Hud', wannan Sura sunanta kenan cikin *Masahif*da littattafan tafsiri da na hadisi. Kuma an kira ta da wannan suna a cikin hadisin Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) inda yake cewa: Abubakar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Ya Ma'aikin Allah, kanka ya yi furfura." Sai ya ce masa: "*Suratu Hud*ce ta sa ni furfura, ita da *Waƙi'a*da *Mursalat*da *Amma*da kuma *Izas Shamsu Kuwwirat*." [Tirmizi #3297]. Hadisin Mursal ne. [Dubi, Ad-Daraƙuɗni, Al-Ilal, Juzi'na 1, shafi na 197, Hadisi na17].

An Karɓo daga Uƙbatu ɗan Amiru (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Na ce wa Manzon Allah (ﷺ) ya karanta mini *Suratu Hud*da *Yusuf*…." [Ahmad#17418, Nasa'i#953].

Malamai sun ce, an kira ta da wannan suna ne saboda ambaton Annabi Hudu da sunansa ya maimaitu a Surar har sau biyar. Hakanan a cikinta ne ƙissarsa ta zo da tsawo fiye da ko'ina.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
A wajen ɗaukacin malamai Sura ce *Makkiyya*baki ɗayanta. Amma akwai ruwaya daga Abdullahi ɗan Abbas da Katadatu inda suka ce, Surar dukkanta *Makkiyya*ce in ban da aya ta (114). Malam Ibnu Aɗiyya kuma a littafin tafsirinsa "*Al-muharrarul Wajiz*" ya ce: ayoyi uku daga cikinta *Madaniyya*ne, su ne aya ta (12) da ta (17) da ta (114).
Amma magana mafi inganci ita ce dukkan ayoyinta Makkiyyane.

3. Jerin Saukarta:
An saukar da wannan Sura bayan "*Suratu Yunus*". A jerin saukar surorin Alƙur'ani ita ce Sura ta hamsin da biyu (52).

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyin wannan Sura a lissafin mutanen Kufa da Basra ɗari da ashirin da uku ne (123). Amma a lissafin mutanen Sham da na Madina (na farko) ayoyinta ɗari da ashirin da biyu ne (122), a lissafin mutanen Madina (na biyu) kuwa ayoyinta ɗari da ashirin da ɗaya ne (121).

5. Babban Jigonta:
- Bayanin tafarkin manzannin Allah wajen fuskantar masu ƙaryata su.
- Karfafa wa Annabi (ﷺ) gwiwa da lallashin sa.

6. Daga Abubuwan Da Surar Ta Kunsa Akwai:
- Bayanin girman Alƙur'ani da tabbatar da cewa saukakke ne daga Allah.
- Bayanin cewa Allah yana sane da duk abin da bayinsa suka ɓoye a zukatansu, kuma shi ne mai ba wa kowa arzikinsa.

• Tabbatar da rayuwa bayan mutuwa da sakamakon ayyukan bayi.
• Lallashin Annabi (ﷺ) da kwantar masa da hankali, ta hanyar nuna cewa, duk abin da ya same shi ya samu sauran ‘yan’uwansa manzanni gabaninsa, amma daga ƙarshe Allah ya taimaka musu ya ba su nasara.
• Bayanin halin kafirai da na muminai.
• Bayani a kan cewa, tsayawa kyam a kan addini da rashin karkata ga azzalumai da tsayar da salla su ne abubuwan da za su samar wa ɗan’adam jin daɗi na duniya da na lahira.

Suratu Hud (1-5)

الٓرۚ كِتَٰبٌ أُحۡكِمَتۡ ءَايَٰتُهُۥ ثُمَّ فُصِّلَتۡ مِن لَّدُنۡ حَكِيمٍ خَبِيرٍ ١ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّا ٱللَّهَۚ إِنَّنِي لَكُم مِّنۡهُ نَذِيرٞ وَبَشِيرٞ ٢ وَأَنِ ٱسۡتَغۡفِرُواْ رَبَّكُمۡ ثُمَّ تُوبُوٓاْ إِلَيۡهِ يُمَتِّعۡكُم مَّتَٰعًا حَسَنًا إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى وَيُؤۡتِ كُلَّ ذِي فَضۡلٖ فَضۡلَهُۥۖ وَإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٖ كَبِيرٍ ٣ إِلَى ٱللَّهِ مَرۡجِعُكُمۡۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ٤ أَلَآ إِنَّهُمۡ يَثۡنُونَ صُدُورَهُمۡ لِيَسۡتَخۡفُواْ مِنۡهُۚ أَلَا حِينَ يَسۡتَغۡشُونَ ثِيَابَهُمۡ يَعۡلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعۡلِنُونَۚ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ***ALIF LAM RA (Wannan) Littafi ne da aka kyautata ayoyinsa sannan aka bayyana su filla-filla, daga wurin Mai hikima, Masani***.

2. Da cewa kada ku bauta wa kowa sai Allah. (Ka ce): ‘‘Lalle ni mai yi muku gargaɗi ne mai albishir daga gare Shi (Allah).

3. ‘‘Kuma da cewa, ku nemi gafarar Ubangijinku sannan ku tuba gare Shi, zai jiyar da ku daɗi, kyakkyawar jiyarwa zuwa wani lokaci ƙayyadadde, Ya kuma bai wa duk wani wanda Ya yi abin kirki (sakamakon) kirkinsa. Idan kuwa kuka ba da baya, to lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wani yini mai girma.

4. ‘‘Zuwa ga Allah ne makomarku; Shi kuwa Mai iko ne a kan komai.’’

5. Ku saurara! Lalle su suna karkatar da ƙirazansu don su ɓoye masa (Allah). Ku saurara! Ai lokacin da suke lulluɓa da tufafinsu Yana sane da abin da suke ɓoyewa da kuma abin da suke bayyanawa. Lalle Shi (Allah) Masanin abin da yake cikin zukata ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da wasu haruffa, kamar yadda ya saba yi a wasu surori da suka gabace ta, domin tabbatar da muʾujizar wannan Littafi, watau Alƙurʾani, ya kuma nuna wa Larabawa cewa su kawo wata magana kwatankwacinsa a fasaha da shiriya in har za su iya, kamar yadda wasu malamai suka bayyana.
Allah ya bayyana cewa, wannan Alƙurʾani wani babban littafi ne wanda aka kyautata ayoyinsa ta fuskar fasahar zance da adalcin hukunce-hukunce, babu wata tawaya ko giɓi a cikinsa, sannan aka rarrabe bayanin da ke cikin ayoyin daki-daki, komai aka aje shi a muhallinsa, domin ya zo ne daga wurin Allah Gwani mai hikima, masanin sarari da ɓoye.
Allah kuma ya bayyana wata babbar hikimar da ke cikinsa, watau ta umartar mutane su bauta wa Allah shi kaɗai ba tare da sun haɗa shi da komai ba. Don haka ya umarci Manzon Allah (ﷺ) ya bayyana wa mutane cewa, shi mai gargaɗi ne daga Allah ga masu saɓa masa game da azabarsa a duniya da lahira, kuma mai yi musu albishir da kyakkyawan sakamako idan sun bi shi sun kaɗaita shi da bauta.

Sannan ya umarci Annabi da ya faɗa wa mutane cewa su nemi gafarar zunubansu a wurin Allah, su tuba su yi nadama a kan laifukan da suka yi, su kuma aikata abin da zai sa ya yarda da su; idan sun yi hakan to Allah zai jiyar da su daɗin duniya har zuwa ƙarewar ajalinsu, kuma duk waɗanda suka yi kyawawan ayyukan ɗa'a za a ba su sakamakon aikinsu cikakke babu tawaya; to amma idan suka bijire masa suka bi soye-soyen zukatansu, to ya faɗa musu cewa, yana jiye musu tsoron wata mummunar azaba a lahira da take jiran su. Kuma dukkansu makomarsu zuwa ga Allah ne ranar alƙiyama, kuma shi mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana jahilcin mushirikai da wautarsu, watau yadda suke karkata ƙirazansu wai domin su ɓoye wa Allah abin da suke ciki na shakka da tababa game da addininsa; a zatonsu Allah ba zai san halin da suke ciki ba. Amma Allah ya tabbatar musu cewa, ai ya san duk halin da suke ciki ko da lokacin da suke lulluɓe kawunansu da tufafinsu ne; yana sane da duk abin da kowa yake ɓoyewa da wanda yake bayyanawa. Hasali ma ya san duk abin da yake cikin zukatansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin yalwar ilimin Allah, kuma da cewa shi kaɗai ne mai arzutawa kuma mai talautawa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci bayi ne domin ya umarce su da bauta masa shi kaɗai ba tare da sun haɗa shi abokin tarayya ba.

3. Bai dace ba wani ya rudu da saurarawar da Allah yake yi masa, ya ɗauka cewa babu wata rana ta sakamako. Allah yana saurara wa masu laifuka ne domin ya kama su ba zato ba tsammani.

4. Bayanin halin ɗan'adam na saurin mancewa da Allah da butulce wa ni'imominsa.

5. Bayanin mummunan halin ɗan'adam na ji-ji da kai da fariya da wulaƙanta mutane don ganin Allah ya yi masa wata ni'ima.

6. Imani da haƙuri a kan ɗa'ar Allah da kyawawan ayyuka su ne suke tsarkake mutum daga wasu miyagun ɗabi'u da halaye da mutum yake da su.

Suratu Hud (6-11)

*وَمَا مِن دَآبَّةٍ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا وَيَعۡلَمُ مُسۡتَقَرَّهَا وَمُسۡتَوۡدَعَهَاۚ كُلّٞ فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ۝٦ وَهُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ وَكَانَ عَرۡشُهُۥ عَلَى ٱلۡمَآءِ لِيَبۡلُوَكُمۡ أَيُّكُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗاۗ وَلَئِن قُلۡتَ إِنَّكُم مَّبۡعُوثُونَ مِنۢ بَعۡدِ ٱلۡمَوۡتِ لَيَقُولَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ مُّبِينٞ ۝٧ وَلَئِنۡ أَخَّرۡنَا عَنۡهُمُ ٱلۡعَذَابَ إِلَىٰٓ أُمَّةٖ مَّعۡدُودَةٖ لَّيَقُولُنَّ مَا يَحۡبِسُهُۥٓۗ أَلَا يَوۡمَ يَأۡتِيهِمۡ لَيۡسَ مَصۡرُوفًا عَنۡهُمۡ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ۝٨ وَلَئِنۡ أَذَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ مِنَّا رَحۡمَةٗ ثُمَّ نَزَعۡنَٰهَا مِنۡهُ إِنَّهُۥ لَيَـُٔوسٞ كَفُورٞ ۝٩ وَلَئِنۡ أَذَقۡنَٰهُ نَعۡمَآءَ بَعۡدَ ضَرَّآءَ مَسَّتۡهُ لَيَقُولَنَّ ذَهَبَ ٱلسَّيِّـَٔاتُ عَنِّيٓۚ إِنَّهُۥ لَفَرِحٞ فَخُورٌ ۝١٠ إِلَّا ٱلَّذِينَ صَبَرُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٞ كَبِيرٞ ۝١١

6. Kuma babu wata dabba a ban ƙasa face arzikinta yana hannun Allah, kuma Yana sane da matabbatarta da ma'ajiyarta. Dukkanin wannan yana nan a cikin littafi mabayyani (shi ne Lauhul Mahafuzu).

7. Shi ne kuma wanda Ya halicci sammai da ƙasa cikin kwana shida, Al'arshinsa kuwa ya kasance a kan ruwa, don Ya jarraba ku a cikinku wa ya fi kyakkyawan aiki. Kuma tabbas idan ka ce (da su): "Lalle za a tashe ku bayan mutuwa," tabbas kafirai za su ce: "Ai wannan ba wani abu ba ne sai tsafi mabayyani."

8. Kuma tabbas da Mun jinkirta musu azaba zuwa wani lokaci ƙayyadadde, lalle za su ce: "Me ya tsare ta?" Ku saurara! Ranar da za ta zo musu ba za a kawar da ita daga kansu ba, kuma abin da suke yi wa izgili zai tabbata a kansu.

9. Kuma tabbas idan Muka ɗandana wa mutum wata rahama daga gare Mu sannan Muka karɓe ta daga gare shi, lalle shi mai yawan yanke ƙauna ne, mai kuma yawan kafirci.

10. Lalle kuma idan Muka ɗandana masa dadi bayan ya sha wahala da ta same shi, tabbas zai riƙa cewa: "Ai munanan (abubuwa) sun bar ni." Lalle shi mai farin ciki ne mai yawan alfahari.

11. Sai dai waɗanda suka yi haƙuri suka kuma yi aiki nagari, waɗannan suna da gafara da kuma lada mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana faffaɗan iliminsa wanda ya haɗe sama da ƙasa da duk abin da suka ƙunsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu wata halitta mai tafiya a bayan ƙasa, mutum ne ko dabba, ta ruwa ko ta tudu, face cinta da shanta yana hannun Allah. Ya kuma san wurin zamansu da wurin tafiye-tafiyensu da kai-kawonsu, ya san inda za su mutu a binne su; duk wannan yana nan a rubuce cikin littafin Lauhul Mahfuzu.
Sai kuma ya ba da labarin cewa, shi ne ya halicci sammai da ƙasa cikin kwana shida; ya fara halitta a ranar Lahadi ya ƙare a ranar Juma'a, kuma Al'arshinsa ya kasance a kan ruwa kafin halittar sammai da ƙasa.

An karɓo daga Imrana ɗan Husaini (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya ku Banu Tamim, albishirinku!" Sai suka ce: "Lalle ka yi mana albishir, sai ka ba mu." Sai ya ce: "Ya ku mutanen Yaman albishirinku!" Sai suka ce: "Mun karɓi albishir, sai ka ba mu labarin farkon wannan al'amari (watau farkon halitta) yaya ya kasance?" Sai ya ce: "Tun kafin halittar komai akwai Allah, kuma Al'arshinsa ya kasance a kan ruwa, ya rubuta ambaton komai a cikin Lauhul Mahfuz." [Bukhari #7418].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah ya ƙaddara abubuwan ƙaddara na halitta tun kafin ya halicci sammai da ƙasa da shekara dubu hamsin, kuma Al'arshinsa ya kasance a kan ruwa." [Muslim #2653].

Bayan haka sai ya ɗaukaka bisa Al'arshinsa yana gudanar da hukunce-hukuncensa na shari'a da na ƙaddara yadda ya ga dama, domin ya jarraba halittunsa ya bayyana wanda ya fi kyakkyawan aiki, watau wanda ya fi ikhlasi cikin aikinsa da koyi da sunna, ya yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa.
Kuma ya bayyana yadda kafirai suke jayayya da Manzon Allah (ﷺ) a kan tashin alƙiyama; duk lokacin da Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa musu cewa, lalle za a tashe su daga ƙaburburansu bayan mutuwarsu domin yi musu hisabi a gaban Allah, to sai su riƙa rantsuwa suna cewa, wannan maganar da yake karanta musu a Alƙur'ani ba wani abu ne ba face tsafi bayyananne, don haka sai su ƙaryata shi su ƙi ba da gaskiya.
Sannan kuma ya bayyana wani salo da kafirai suka riƙa bi wajen ƙaryata Manzon Allah (ﷺ), shi ne idan ya faɗa musu cewa, Allah na iya saukar musu da azaba idan sun ƙi yin imani da shi. To yayin da Allah ya jinkirta musu wannan azabar sai su kafa hujja da wannan jinkirin su ce da ma Annabi ƙarya yake faɗa musu, wai in ba haka ba me ya hana azabar ta sauko musu? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, ranar da azabar za ta zo musu babu mai iya juyar da wannan ranar ta fasa zuwa, kuma abin da suke izgili da shi na azaba shi ne zai auka musu a wannan ranar.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin halin ɗan'adam yayin da Allah ya ni'imta shi da wasu ni'imomi na dukiya ko lafiya ko 'ya'ya ko dai wani abu na jin daɗin rayuwar duniya sannan daga baya Allah ya karɓe wannan ni'imar daga hannunsa, to sai ya rikice ya zama mai ɗebe ƙauna gaba ɗaya, ya

riƙa ganin babu yadda za a yi wannan ni'imar ta sake dawo masa, ya kuma zama mai yawan kafirci, ya ƙi komawa ga Allah ya nemi taimako da ƙaskantar da kai a gabansa.
Haka kuma idan Allah ya yi masa wata ni'ima bayan wata wahala da yake ciki a da, ba zai tuna cewa Allah ne ya yaye masa wahalar da yake ciki ba, ya ba shi wannan ni'imar, sai dai kawai ya riƙa cewa, wahalhalu sun rabu da shi, ba zai gode wa Allah ba sai dai ya yi ta ji-ji da kai yana fariya da cika baki da ni'imar da yake ciki.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi togaciyar masu haƙuri a kan bin Allah da barin saɓon sa, waɗanda suka yi ayyuka na ƙwarai, to waɗannan ba sa kamuwa da cutar fitar da ƙauna ko kafirce wa ni'imomin Allah ko ji-ji da kai da wulaƙanta mutane. Masu irin wannan hali Allah ya tanadar musu gafara da lada mai girma a ranar lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai ba wa Annabi (ﷺ) damar canza wani abu daga addininsa ba don ya faranta wa kafirai rai. Don haka babu wanda yake da ikon aikata hakan don dadaɗa wa wasu a kowane wuri a kuma kowane zamani, komai matsayin mutum kuwa.

2. Tsananin ƙaunar Annabi (ﷺ) ga al'ummarsa ya sa fanɗarewarsu take matuƙar damun sa.

3. Alƙur'ani littafi ne gagara-koyo, kuma mu'ujiza ce ta Annabi (ﷺ) ga duk duniya, kuma mai ɗorewa har tashin alƙiyama.

4. Kasa karɓar ƙalubale da Larabawa suka yi a kan su kwaikwayi Alƙur'ani babban dalili ne da ya wajaba ya ƙara wa muminai imani da tabbatar da cewa Alƙur'ani maganar Allah ne.

5. A cikin waɗannan ayoyi akwai koyarwa ga mai da'awa a kan cewa, kada gardamar masu gardama ta sa da'awarsa ta tsaya cak; ya kamata wannan ya ƙara masa nutsuwar zuciya da ƙarfin gwiwa a kan da'awarsa.

Suratu Hud (12-14)
فَلَعَلَّكَ تَارِكُۢ بَعۡضَ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيۡكَ وَضَآئِقُۢ بِهِۦ صَدۡرُكَ أَن يَقُولُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ كَنزٌ أَوۡ جَآءَ مَعَهُۥ مَلَكٌۚ إِنَّمَآ أَنتَ نَذِيرٞۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٌ ١٢ أَمۡ يَقُولُونَ ٱفۡتَرَىٰهُۖ قُلۡ فَأۡتُواْ بِعَشۡرِ سُوَرٖ مِّثۡلِهِۦ مُفۡتَرَيَٰتٖ وَٱدۡعُواْ مَنِ ٱسۡتَطَعۡتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ١٣ فَإِلَّمۡ يَسۡتَجِيبُواْ لَكُمۡ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَآ أُنزِلَ بِعِلۡمِ ٱللَّهِ وَأَن لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّسۡلِمُونَ ١٤

12. To yanzu za ka bar wani abu daga abin da ake yi maka wahayi da shi, kuma zuciyarka za ta ƙuntata da shi don kawai za su ce: "Me ya hana a saukar masa da wata taska, ko kuma wani mala'ika ya zo tare da shi?" Kai dai mai gargaɗi ne kawai. Allah kuma Wakili ne a kan komai.

13. A'a, ko cewa suka yi: "Ya ƙirƙire shi ne?" Ka ce: "Ku kawo sura goma kamarsa ƙagaggu, kuma ku kira duk wanda za ku iya wanda ba Allah ba (ya taimake ku) in kun kasance masu gaskiya."

14. To idan ba su amsa muku ba, to ku tabbatar cewa lalle an saukar da shi ne (Alƙur'ani) da sanin Allah, kuma babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, To shin yanzu za ku miƙa wuya?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙara lallashin Manzonsa ne game da taurin kai da yake fuskanta na Ƙuraishawa da wasu maganganu na izgili da suke faɗa masa da son su ƙure shi, har suna neman ya canza Alƙur'ani ko wasu ayoyinsa, ya zo musu da abin da bai saɓa wa son zuciyarsu ba; idan ya

yi haka to za su yi imani da shi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa wata tambaya ta kashedi da cewa, yanzu zai iya barin wani abu da Allah ya yi masa wahayin sa ya daina karanta musu shi? Kuma zuciyarsa za ta ƙuntata ne don kawai suna cewa, me ya hana a saukar masa da wata taska ta dukiya daga sama ya zama cikin manyan masu kuɗin Larabawa, ko kuma wani mala'ika ya zo yana yawo tare da shi yana gaskata shi idan yana yi musu wa'azi? Allah a nan yana hana shi ya saurare su a kan waɗannan maganganu nasu na banza, yana nuna masa cewa, shi fa kawai mai gargaɗi ne kuma Allah shi ne wakili a kan komai, shi yake tsare da ayyukansu kuma shi ne mai yi musu sakamako a kansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, maganar da mushirikai suke ta nanatawa koyaushe ita ce, wai Annabi (ﷺ) ne ya ƙirƙiri Alƙur'ani ba wahayi ne daga Allah ba. To in hakan gaskiya ne, wannan ya nuna mutane za su iya kawo kamar Alƙur'ani, to ya ƙalubalance su cewa su ma su kawo ƙirƙirarrun surori goma kamarsa, su kuma nemi duk wanda zai taimaka musu a kan haka ba Allah ba in dai har gaskiya suke faɗi cewa shi ne ya ƙirƙiro Alƙur'ani.
To babu shakka ba za su iya amsa wannan ƙalubalen ba. To idan suka kasa, su muminai su san da cewa an saukar da Alƙur'ani ne da ilimin Allah wanda shi ne ya san komai da kowa, kuma ba Annabi ne ya ƙage shi ba, sannan su tabbatar da cewa babu wani abin bauta da gaskiya sai Allah. Anya kuwa za su miƙa wuya su ba da gaskiya bayan bayyanar waɗannan hujjoji?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi ga masu fifita rayuwar duniya a kan ta lahira.

2. Duk wanda ya nemi duniya, ya kuma bi hanyoyin da Allah ya tanada don samun ta, to Allah na iya hore masa samun ta ko da kuwa shi ba mumini ne ba. To amma wannan shi ne ƙarshen ladansa, a lahira ba shi da komai sai wutar Jahannama.

3. Duk wanda bai yi imani da Allah da Manzonsa ba, to a nan duniya ne kawai Allah zai biya shi ladan ayyukan da ya yi na ƙwarai, kamar taimakon mutane ko sada zumunci da makamantansu, a lahira ba shi da komai sai azaba.

4. Littattafan annabawa da suka gabata duk suna shaidar gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ) da ingancin Alƙur'ani.

5. Duk wanda bai yi imani da Manzon Allah ba bayan aiko shi, kuma saƙonsa ya isa gare shi, to wannan ba zai shiga Aljanna ba idan ya mutu yana a kan addininsa bai musulunta ba.

Suratu Hud (15-17)

مَن كَانَ يُرِيدُ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا وَزِينَتَهَا نُوَفِّ إِلَيۡهِمۡ أَعۡمَٰلَهُمۡ فِيهَا وَهُمۡ فِيهَا لَا يُبۡخَسُونَ ١٥ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَيۡسَ لَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ إِلَّا ٱلنَّارُۖ وَحَبِطَ مَا صَنَعُواْ فِيهَا وَبَٰطِلٞ مَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٦ أَفَمَن كَانَ عَلَىٰ بَيِّنَةٖ مِّن رَّبِّهِۦ وَيَتۡلُوهُ شَاهِدٞ مِّنۡهُ وَمِن قَبۡلِهِۦ كِتَٰبُ مُوسَىٰٓ إِمَامٗا وَرَحۡمَةًۚ أُوْلَٰٓئِكَ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۚ وَمَن يَكۡفُرۡ بِهِۦ مِنَ ٱلۡأَحۡزَابِ فَٱلنَّارُ مَوۡعِدُهُۥۚ فَلَا تَكُ فِي مِرۡيَةٖ مِّنۡهُۚ إِنَّهُ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يُؤۡمِنُونَ ١٧

15. Waɗanda suke nufin rayuwar duniya da ƙawace-ƙawacenta, to za Mu ba su cikakken sakamakon ayyukansu a cikinta, kuma ba za a tauye musu (komai ba).

16. Waɗannan su ne waɗanda ba su da komai a lahira sai wuta; kuma abin da suka aikata a cikinta (duniyar) ya rushe, kuma abin da suke aikatawa ya lalace.

17. Shin yanzu wanda yake a kan hujja daga Ubangijinsa, kuma wani mai ba da shaida yana biye da shi (Alƙurʾani); a gabaninsa kuma akwai Littafin (Annabi) Musa (wanda yake) abin koyi ne, kuma rahama ne, (zai yi daidai da wanda ba haka ba)? Waɗannan suna yin imani da shi. Daga sauran ƙungiyoyi kuma duk wanda ya kafirce da shi, to fa wuta ce makomarsa. Don haka kada ka kasance cikin kokwanto game da shi (Alƙurʾani). Lalle shi gaskiya ne daga Ubangijika yake, sai dai kuma yawancin mutane ba sa yin imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, duk wanda jin daɗîn duniya da ƙyale-ƙyalenta yake nufi da aikinsa na ƙwarai ba gidan lahira ne a gabansa ba, to masu wannan niyyar Allah zai cika musu ladansu a nan duniya, ya ba su lafiya da zaman lafiya da dukiya, ba zai rage musu komai ba, to amma fa waɗannan a lahira ba su da wani sakamako sai wuta wadda za su shige ta su dawwama a cikinta har abada, duk wani aikin kirki da suka yi a nan duniya ya rushe, a lahira ba ya da wata ƙima, domin ba su yi shi don Allah ba, babu kuma kyakkyawar niyya tare da su.

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah ba ya zaluntar mumini a wani aikinsa na lada, zai ba shi sakamakonsa a duniya, kuma ya ba shi a lahira. Amma kafiri sai Allah ya ciyar da shi a duniya a dalilin kyawawan ayyukansa da ya yi don Allah, har sai ya mutu a ranar lahira zai zo ba shi da sauran wani aikin ƙwarai." [Muslim #2808].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya bai wa Annabi Muhammadu (ﷺ) wata hujja daga gare shi, kuma Malaʾika Jibrilu, ya shaidi haka sannan littafin Attaura da Allah ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ma yana yi masa shaida a kan gaskiyar annabcinsa, muminan da suka yi imani da shi ma sun shaida. To ta yaya za a gwada shi da sauran kafirai waɗanda suke fagamniya a cikin ɓata. Muminai su kam sun yi imani da Alƙurʾanin da Annabi Muhammadu (ﷺ). Duk kuwa wanda ya kafirce wa Manzon Allah (ﷺ) daga masu bin sauran addinai, to wutar Jahannama ce makomarsa ranar alƙiyama.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ashʾari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Na rantse da wanda raina yake a hannunsa, babu wani daga cikin wannan alʾumma da zai samu labarina, Bayahude ne shi ko Banasare, sannan ya ƙi yin imani da ni, sai ya shiga wuta." [Muslim #153].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) kashedi kada ya ɗarsa wata shakka game da Alƙurʾani ko kuma makomar masu ƙaryata shi, domin wannan gaskiya ce da babu wani kokwanto a cikinta, sai dai kawai mutane ba sa yin imani ne duk kuwa da yawan dalilai da hujjoji gamsassu a kan haka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman zaluncin wanda ya ƙirƙiri ƙarya ya jingina wa Allah, kamar masu daʾawar Allah yana da ɗa, ko daʾawar annabta, ko jingina wa Allah halatta abin da bai halatta ba, ko haramta abin da bai haramta ba.

2. Maƙiya gaskiya a koyaushe suna ƙoƙarin su ɓata ta a idon mutane don su hana su yarda da ita, kamar yadda suke ƙoƙarin ganin sun ɓata sunan mai daʾawa domin su sanya mutane tsanar sa a zukatansu, su riƙa gudun sa da ƙin karɓar daʾawarsa.

3. Duk wanda ya ɓace kuma ya ɓatar da wasu to azabarsa ninki biyu ce a lahira.

4. Jin kafirai da ganinsu ba su da amfani a wurinsu domin sun kasa jin gaskiya sun kasa ganin ta.

وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ يُعْرَضُونَ عَلَىٰ رَبِّهِمْ وَيَقُولُ ٱلْأَشْهَٰدُ هَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ كَذَبُوا۟ عَلَىٰ رَبِّهِمْ ۚ أَلَا لَعْنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٨﴾ ٱلَّذِينَ
يَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَيَبْغُونَهَا عِوَجًا وَهُم بِٱلْءَاخِرَةِ هُمْ كَٰفِرُونَ ﴿١٩﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ لَمْ يَكُونُوا۟ مُعْجِزِينَ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا كَانَ لَهُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِنْ أَوْلِيَآءَ
يُضَٰعَفُ لَهُمُ ٱلْعَذَابُ ۚ مَا كَانُوا۟ يَسْتَطِيعُونَ ٱلسَّمْعَ وَمَا كَانُوا۟ يُبْصِرُونَ ﴿٢٠﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿٢١﴾ لَا جَرَمَ أَنَّهُمْ
فِى ٱلْءَاخِرَةِ هُمُ ٱلْأَخْسَرُونَ ﴿٢٢﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَأَخْبَتُوٓا۟ إِلَىٰ رَبِّهِمْ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿٢٣﴾ ۞ مَثَلُ ٱلْفَرِيقَيْنِ
كَٱلْأَعْمَىٰ وَٱلْأَصَمِّ وَٱلْبَصِيرِ وَٱلسَّمِيعِ ۚ هَلْ يَسْتَوِيَانِ مَثَلًا ۚ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴿٢٤﴾

18. Kuma ba wanda ya fi zalunci kamar wanda ya ƙirƙira wa Allah ƙarya. Waɗannan za a kawo su a gaban Ubangijinsu, shaidu kuma (wato mala'iku) su ce: "Waɗannan su ne suka yi wa Ubangijinsu ƙarya. Ku saurara, la'anar Allah ta tabbata a kan azzalumai.

19. "Waɗanda suke hana bin hanyar Allah, suna kuma son ta a karkace; kuma su ne masu kafircewa da ranar lahira."

20. Waɗannan ba su zamo masu gagara ba a bayan ƙasa, kuma ba su da masu jiɓintar lamarinsu waɗanda ba Allah ba, (kuma) za a ninka musu azaba. Ba su kasance sun iya jin (gaskiya) ba, ba su kuma zamanto masu iya ganin (ta) ba.

21. Waɗannan su ne waɗanda suka yi asarar kawunansu. Abin da suke ƙirƙira kuma ya ɓace musu.

22. Ba shakka lalle su ne suka fi asara a lahira.

23. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, suka kuma ƙasƙantar da kansu ga Ubangijinsu to waɗannan su ne 'yan Aljanna, su masu dawwama ne a cikinta.

24. Misalin jama'ar nan guda biyu (mumini da kafiri) kamar makaho ne da kurma da kuma mai gani da mai ji. Shin ga misali za su zama daidai kuwa? To me ya sa ba za ku wa'azantu ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai maƙaryata za su kunyata a lahira a gaban ɗaukacin halitta, kuma babu azzalumin mutum kamar wanda zai ƙagi ƙarya ya jingina wa Allah, kamar masu jingina masa dà ko abokin tarayya; to irin waɗannan mutane za a kawo su gaban Ubangijinsu a ranar alƙiyama domin ya yi musu tambayoyi a kan ayyukansu; to a nan ne mala'iku da manzanni masu bayar da shaida za su ce, waɗannan su ne suka ƙirƙira wa Allah ƙarya. Lalle kuma la'anar Allah, watau kora daga rahamarsa, ta tabbata ga mutane azzalumai waɗanda suka zalunci kawunansu da yi wa Allah ƙarya.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Allah zai matso da mumini kusa da shi sai ya suturta shi ya kuma ce masa: "Shin kana tuna zunubi iri kaza da zunubi iri kaza?" Shi kuma yana cewa: "E, ya Ubangijina." Har sai ya amsa duk laifukansa, ya kuma tabbatar ya halaka, sai Allah ya ce masa: "Na rufa maka asiri a kansu a duniya, to a yau ma na gafarta maka su." Sai a ba shi littafin kyawawan ayyukansa. To amma kafirai da munafukai sai masu shaida su ce: "Waɗannan su ne suka yi wa Ubangijinsu ƙarya, to la'anar Allah ta tabbata a kan azzalumai." [Bukhari #2441 da Muslim #2768].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin waɗannan azzalumai da cewa, su ne waɗanda suke hana mutane bin hanyar Allah miƙaƙƙiya, suke son koyaushe su gan ta a karkace domin mutane su ƙyamaci

bin ta, kuma suna kafirce wa ranar lahira, domin suna ƙaryata zuwanta, to shi ne Allah yake tabbatar musu da cewa ba za su taɓa gagarar sa ba, domin a duk inda suke suna ƙarƙashin mulkinsa ne da gamammen ikonsa, don haka zai iya damƙar su tun a nan duniya kafin a je lahira, domin kuwa ba su da wasu masu taimakon su su kare su daga damƙar Ubangiji. A lahira kuwa za a riɓanya musu azaba ne, saboda bayan kafircewarsu, sun kuma karkatar da wasu daga bin hanyar Allah, domin a nan duniya sun ƙi nutsuwa su saurari gaskiyar da ake faɗa musu, sannan kuma sun ƙi yin tunani cikin ayoyin Allah da ke shimfiɗe a cikin halittunsa domin su ɗauki izina da darasi daga gare su. To waɗannan su ne suka yi asarar kawunansu, suka jefa kansu cikin halaka ta hanyar rungumar wasu gumaka a matsayin ababen tarayya da Allah. To a ranar lahira za su neme su su rasa su; za su ɓace musu ɓat, domin da man na ƙarya ne ba na gaskiya ba.
Allah ya sake tabbatar musu da cewa, lalle su ne asararru a ranar alƙiyama, domin sun fifita kafirci a kan imani, sun zaɓi azaba maimakon rahama.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ɗaya ɓangaren, watau muminai da cewa, waɗanda suka ba da gaskiya da Allah da shika-shikan imani, kuma suka yi kyawawan ayyuka, suka ƙasƙantar da kansu ga Allah, to waɗannan su ne ‘yan Aljanna masu dawwama a cikinta har abada.
Sannan Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin ƙungiyar kafirai da jamaʾar Musulmi, inda ya kwatanta su da makahon da yake dinɗim ba ya ganin komai ko kurman da ba ya ji kwata-kwata, ya kuma kwatanta Musulmi da mutumin da yake gani tar kuma yake ji sarai, shin waɗannan jamaʾu biyu na kafirai da muminai za su taɓa zama daidai? Babu shakka duk mai hankali ya san ba za su daidaita ba. To me ya sa kafirai ba sa waʾazantuwa ne su fahimci bambancin da ke tsakanin imani da kafirci ko mumini da kafiri?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Irin maganganun da mutanen Annabi Nuhu suka faɗa masa su ne irin waɗanda Ƙuraishawa suka faɗa wa Annabi (ﷺ), na cewa shi mutum ne kamarsu, kuma mabiyansa duk wasu wulaƙantattun mutane ne, kuma babu abin da ya fi su da shi da har za a ba shi annabta ba a ba su ba; kuma ƙarya ce yake yi wa Allah ba a aiko shi ba.

2. Annabawa mutane ne kamar jinsin sauran mutane, Allah yake zaɓo su domin ya girmama su da wahayinsa da saƙonsa zuwa ga al'ummunsu.

3. Yawancin mabiya annabawa su ne galaɓaitattun mutane matalauta marasa galihu, domin sau da yawa shugabanci da girman matsayi cikin alʾumma yakan hana manyan mutane yarda da gaskiya, domin suna tsoron idan sun yarda da mai kiran su zuwa ga gaskiya, kamar sun rasa shugabancinsu ne da matsayi a tsakanin alʾumma, wannan ne yake sa su bijire.

4. Allah yana duba zukatan bayinsa ne da ayyukansu ya yi musu gamo-da-katar, ba nasabarsu ko usulinsu ba.

Suratu Hud (25-27)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦٓ إِنِّي لَكُمۡ نَذِيرٞ مُّبِينٌ ٢٥ أَن لَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّا ٱللَّهَۖ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٍ أَلِيمٖ ٢٦ فَقَالَ ٱلۡمَلَأُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَوۡمِهِۦ مَا نَرَىٰكَ إِلَّا بَشَرٗا مِّثۡلَنَا وَمَا نَرَىٰكَ ٱتَّبَعَكَ إِلَّا ٱلَّذِينَ هُمۡ أَرَاذِلُنَا بَادِيَ ٱلرَّأۡيِۖ وَمَا نَرَىٰ لَكُمۡ عَلَيۡنَا مِن فَضۡلِۭ بَلۡ نَظُنُّكُمۡ كَٰذِبِينَ ٢٧

25. Haƙiƙa kuma Mun aiko Nuhu zuwa ga mutanensa (ya ce da su): “Lalle ni mai gargaɗi bayyananne ne a gare ku.

26. “Cewa kada ku bauta wa (kowa) sai Allah. Lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wata rana mai raɗaɗi.”

27. Sai manya-manya daga cikin mutanensa, waɗanda suka kafirta suka ce (da shi): “Mu fa mun ɗauke ka kawai mutum ne kamarmu, kuma ba ma ganin wani ya bi ka in ban da wulakantattun cikinmu gidadawa. Kuma ba ma ganin ku da wani fifiko a kanmu; kai muna ma tsammanin ku maƙaryata ne.”

A waɗannan ayoyi da masu zuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana labarta wa Annabinsa (ﷺ) tarihin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda shi ne farkon manzo da Allah ya aiko duniya, tare da sauran annabawa don ya lallashe shi ya kwantar masa da hankali game da ƙaryatawar da mutanensa Ƙuraishawa suke yi masa da izgili da tsangwamar sa shi da mabiyansa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya aiko Manzonsa Annabi Nuhu zuwa ga mutanensa, waɗanda su ne suka fara bautar gumaka bayan Tauhidi da annabawan da suka riga Annabi Nuhu suka karantar. Babban jigon da’awar Annabi Nuhu shi ne bautar Allah shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba, ya nuna musu cewa, idan sun ƙi ba da gaskiya da shi sun ƙi yin watsi da bautar gumakansu, to yana jiye musu tsoron wata azaba mai raɗaɗî da za ta same su daga Allah.
To amma maimakon mutanensa su saurare shi su fahimci gaskiyar da yake faɗa musu, sai kawai manyansu masu faɗa a ji suka ƙaryata shi tare da bayyana wasu hujjoji na ƙaryata shi da cewa:

(a) Shi mutum ne kamarsu, babu wani dalilin da zai sa su bi wani mutum irin jinsinsu.

(b) Mabiyansa wai duk wasu ƙasƙantattun mutane ne marasa galihu cikin jama’a, kuma ga su gidadawa waɗanda ba su yi aiki da tunaninsu ba wajen yarda da shi, kawai sun miƙa masa wuya ne ba tare da wata hujja ba.

(c) Su ba su ga wani abu da Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mabiyansa suka fi su da shi ba har da Allah zai fifita su a kansu; su dai ba ƙarfi suka fi su ba, ba yawan dukiya ko ilimi ko ‘ya’ya ba; ba su fi su usuli ba, to saboda me za su yarda su yi imani da irin waɗannan mutane?
(d) Su sun fi tsammanin cewa Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da jama’arsa kawai maƙaryata ne babu gaskiya tare da su, don haka me zai sa su yarda da maƙaryata haka kawai?

Waɗannan su ne hujjojin bogi da manyan gari suka taka don ƙaryata Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ƙiyayya da hassada sukan rufe wa mutum idanunsa ya kasa ganin gaskiya ballantana ya bi ta.

2. Babu tilastawa a addini. Ƙa’ida ce da ta samo asali tun daga kan annabin Allah na farko, watau Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

3. Mai kira zuwa ga Allah wajibi ne ya cire son abin hannun mutane domin da’awarsa ta samu karɓuwa, shi ma ya tabbata mai cikakken ikhlasi ga Ubangijinsa.

4. Mai da’awa bai dace gare shi ya kori wani daga majalisinsa ba saboda yana yi masa kallon wulaƙanci ko raini.

5. Cutar da waliyyan Allah abu ne mai haɗarin gaske ga bawa, domin hakan zai jawo masa fushin Allah.

6. Babu mai arzutawa sai Allah shi kaɗai, domin taskokin arzuki a hannunsa suke, bai sanya su a hannun kowa ba.

7. Babu wanda ya san gaibu sai Allah. Don haka annabawa ma ba su san gaibu ba, sai abin da Allah ya yi musu wahayinsa.

8. Bai dace a riƙa auna mutum da abin da ake gani tare da shi na ido ba kaɗai, Allah ne ya san abin da zukata suka ƙunsa na alheri ko na sharri.

Suratu Hud (28-31)

قَالَ يَٰقَوۡمِ أَرَءَيۡتُمۡ إِن كُنتُ عَلَىٰ بَيِّنَةٖ مِّن رَّبِّي وَءَاتَىٰنِي رَحۡمَةٗ مِّنۡ عِندِهِۦ فَعُمِّيَتۡ عَلَيۡكُمۡ أَنُلۡزِمُكُمُوهَا وَأَنتُمۡ لَهَا كَٰرِهُونَ ٢٨ وَيَٰقَوۡمِ لَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ مَالًاۖ إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِۖ وَمَآ أَنَا۠ بِطَارِدِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْۚ إِنَّهُم مُّلَٰقُواْ رَبِّهِمۡ وَلَٰكِنِّيٓ أَرَىٰكُمۡ قَوۡمٗا تَجۡهَلُونَ ٢٩ وَيَٰقَوۡمِ مَن يَنصُرُنِي مِنَ ٱللَّهِ إِن طَرَدتُّهُمۡۚ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ٣٠ وَلَآ أَقُولُ لَكُمۡ عِندِي خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ أَعۡلَمُ ٱلۡغَيۡبَ وَلَآ أَقُولُ إِنِّي مَلَكٞ وَلَآ أَقُولُ لِلَّذِينَ تَزۡدَرِيٓ أَعۡيُنُكُمۡ لَن يُؤۡتِيَهُمُ ٱللَّهُ خَيۡرًاۖ ٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا فِيٓ أَنفُسِهِمۡ إِنِّيٓ إِذٗا لَّمِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٣١

28. (Annabi Nuhu) ya ce: “Ya ku mutanena, ku ba ni labari, yanzu idan na zamanto ina riƙe da hujja daga Ubangijina, Ya kuma ba ni wata rahama daga gare Shi, sai aka ɓoye muku ita, yanzu ma tilasta muku ita, alhali kuwa kuna ƙin ta?

29. “Kuma ya ku mutanena, ba na tambayar ku wata dukiya a kansa (kiran); ladana a wurin Allah kawai yake. Ni kuwa ba zan kori waɗanda suka yi imani ba. Lalle su masu saduwa ne da Ubangijinsu, sai dai ni ina ganin ku mutane ne da kuke jahiltar (gaskiya).”

30. “Ya ku mutanena, wa zai kare ni daga Allah idan na kore su? Me ya sa ne ba kwa waʾazantuwa?

31. “Ba kuma zan ce da ku ina da taskokin Allah ba, ban kuma san gaibu ba, kuma ba zan ce lalle ni malaʾika ne ba, ba kuma zan ce wa waɗanda idanuwanku suke wulaƙantawa, Allah ba zai ba su wani alheri ba. Allah ne Ya fi sanin abin da yake zukatansu. Idan na yi haka, to lalle na zamanto daga cikin azzalumai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana amsar da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ba wa mutanensa ne da cewa, su faɗa masa, idan har shi yana kan wata hujja daga Ubangijinsa wadda ta tabbatar da cewa annabcinsa daga gare shi ne, ba shi ne ya naɗa kansa ba, watau Allah ne ya so shi da wannan rahamar ta annabta, amma su suka kasa ganin ta saboda jahilcinsu da ruɗuwarsu da duniya, don haka suka ƙi yin imani da shi, ya ce to zai tilasta musu ne sai dole sun yi imani ko da ba sa so? Ba zai iya yi musu dole ba, domin imani dace ne daga Allah ga wanda ya ga dama.

Sannan ya bayyana musu cewa, maganar ba ta dukiya ce ba, domin shi kansa da yake tallata musu kiransa, ba nema yake su biya shi wata dukiya ba; shi ladansa yana wurin Allah ne, yana neman su da shiriya ne kawai. Sannan waɗannan talakawan da suke sukan su da cewa gidadawa ne marasa tunani, shi ba zai iya korar su daga majalisarsa ba, domin kuwa sun yi imani, sun kuma san cewa za su koma ga Allah ne ranar alƙiyama inda za a tantance tsakaninsu da su, su wane ne suka fi daraja a wurin Allah. Daga ƙarshe Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) dai ya fahimci cewa mutanensa ba su gama gane haƙiƙanin daʾawarsa ba, shi ya sa har suke neman ya kori talakawan da suka yi imani da shi.

Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sake kiran mutanensa ya jaddada musu cewa, idan har ya amince ya kori waɗannan matalauta kamar yadda manyan gari suka neme shi bisa zalunci, to wane ne a cikinsu zai kare shi a gaban Allah idan ya yi nufin azabtar da shi? Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna musu cewa, yanzu me ya sa ne ba za su waʾazantu ba, su yi tunani su fahimci korar su ba alheri ba ne gare shi har da su ma gaba ɗaya? Idan su matalauta ne, to ai shi ma mai buƙata ne a wurin Allah, don haka ya kore wa kansa abubuwa hudu:

(a) Taskokin Allah ba a hannunsa suke ba, ballantana ya ba wa wasu ya hana wasu. Allah ya aiko shi ne ya tsarkake musu zukata ba ya raba musu arzuki ba.

(b) Ya tabbatar musu cewa, shi fa bai san gaibu ba, Allah ne kaɗai ya keɓanta da sanin gaibu, sai dai abin da ya ga dama ya sanar da wanda ya ga dama cikin manzanninsa.

(c) Bai taɓa faɗa musu cewa shi malaʾika ne ba; shi mutum ne kamarsu, a gabansu aka haife shi, sun san shi sun kuma san iyayensa.

(d) Ya tabbatar musu cewa, ba zai taɓa cewa mutanen da suke yi wa kallon wulaƙanci, Allah ba zai taɓa ba su wani alheri ba, watau ya shiryar da su su fahimci gaskiya, Allah kuma shi ya fi sanin niyyoyinsu. Ya ce, idan har ya kuskura ya yi daʾawar waɗannan abubuwa, to lalle ya zama azzalumi wanda ya cancanci azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Masu faɗa da gaskiya sukan canza wa daʾawar mai daʾawa suna don su ɓata shi a idon jamaʾa, kamar yadda mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka kira nasiharsa da ‘jayayya’ da nufin suka gare shi.

2. Shiriya tana hannun Allah, shi ne mai shiryar da wanda ya ga dama, ƙwarewar mai waʾazi ba shi ne ke haifar da shiryuwar bawa ba.

3. A cikin wannan ƙissa akwai hikimomi biyu da Allah ya sanya:

Ta farko: Lallashin Manzon Allah (ﷺ) ta hanyar bayyana masa cewa, abin da yake samun sa ya taɓa samun annabawan da suka gabace shi, to amma daga ƙarshe su ne suke yin nasara.

Ta biyu: Tabbatar da muʾujizar Alƙurʾani, domin yana kawo labaran annabawa da alʾummun da suka gabata, ba tare da wani malami ya koyar da Manzon Allah (ﷺ) ko ya karanta a wani littafi ba, wannan gamsasshen dalili ne a kan cewa Alƙurʾani wahayi ne daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Hud (32-35)

قَالُواْ يَٰنُوحُ قَدۡ جَٰدَلۡتَنَا فَأَكۡثَرۡتَ جِدَٰلَنَا فَأۡتِنَا بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ٣٢ قَالَ إِنَّمَا يَأۡتِيكُم بِهِ ٱللَّهُ إِن شَآءَ وَمَآ أَنتُم بِمُعۡجِزِينَ٣٣ وَلَا يَنفَعُكُمۡ نُصۡحِيٓ إِنۡ أَرَدتُّ أَنۡ أَنصَحَ لَكُمۡ إِن كَانَ ٱللَّهُ يُرِيدُ أَن يُغۡوِيَكُمۡۚ هُوَ رَبُّكُمۡ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ٣٤ أَمۡ يَقُولُونَ ٱفۡتَرَىٰهُۖ قُلۡ إِنِ ٱفۡتَرَيۡتُهُۥ فَعَلَيَّ إِجۡرَامِي وَأَنَا۠ بَرِيٓءٞ مِّمَّا تُجۡرِمُونَ٣٥

32. Suka ce: “Ya Nuhu, haƙiƙa ka ja da mu, ka kuma yawaita jayayya da mu; to sai ka zo mana da abin da kake yi mana alƙawari da shi (na narko) in ka zamo daga masu gaskiya.”

33. Ya ce: “Ai Allah ne zai zo muku da shi idan Ya ga dama, ku kuma ba za ku gagara ba.

34. “Nasihata kuma ba za ta amfane ku ba - ko da na yi nufin yi muku nasihar - idan har da ma can Allah Yana nufin Ya ɓatar da ku. Shi ne Ubangijinku, kuma wurinsa za ku koma.”

35. A’a, ko dai cewa suke: “Ƙagar sa ya yi?” (wato Alƙur’ani) Ka ce: “Idan ƙagar sa na yi, to alhakin ƙagena yana kaina ne, ni kuma ba ruwana da laifin abin da kuke tabkawa.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da bayanin ƙissar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa, bayan duk irin hujjoji da ya kawo musu domin ya shawo kansu su ba da gaskiya, sai ƙara zaƙewa suke yi cikin tsaurin kai, suka kira waʼazin da yake musu da sunan ‘jayayya’ suka ma nemi ya sa a saukar musu da azabar da yake cewa yana jiye musu tsoron ta, idan har ya tabbata shi mai gaskiya ne.
Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana musu cewa, ai azabar ba a hannunsa take ba, ballantana ya saukar musu da ita kamar yadda suka nema; Allah ne idan ya ga dama sai ya saukar musu da ita a lokacin da ya ga dama, kuma ba za su gagare shi ba ko su kuɓuce masa.
Amma shi Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) aikinsa shi ne ya yi musu nasiha ya faɗa musu gaskiya, to amma ya san nasiharsa kaɗai ba za ta amfane su har su gane halakar da suke ciki ba, matuƙar Allah yana nufin ya ɓatar da su, saboda sun nuna sun fi son ɓatan a kan shiriya, domin shi ne Ubangijinsu komai nasu yana wurinsa, kuma wurinsa kaɗai za su koma don ya yi musu hisabi a kan ayyukansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya juyo da akalar magana zuwa ga mushirikan Ƙuraishawa waɗanda idan sun ji Annabi (ﷺ) yana karanta musu irin waɗannan ƙissoshin masu ɗauke da bayanin halayen kafiran farko waɗanda suka yi kama da nasu, sai su ce Manzon Allah (ﷺ) ne yake ƙagar irin waɗannan ƙissoshin. Shi ne a nan Allah yake cewa, ko suna ganin Annabi ne ya ƙagi wannan labarin da yake faɗa musu? To Manzon Allah ya mayar musu da martani cewa, idan shi ne ma ya ƙage su, to ai shi kaɗai zai ɗauki alhakin yi wa Allah ƙarya ba su ba, domin wani rai ba ya ɗaukar laifin wani, kuma shi ma ya faɗa musu cewa ba ruwansa da laifin da suke tabkawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kada mai daʼawa ya damu kansa da baƙin ciki saboda mutane sun ƙi amsa kiransa, domin wannan ba daga gare shi ne ba, ko daga daʼawarsa; Allah ne bai rubuta musu shiriya ba.

2. Alʼada ce ta kafirai yi wa annabawa da mabiyansu izgili.

3. Darajar masu daraja da nagartarsu ba sa hana jahilai su riƙa yi musu izgili.

4. Bayanin sunnar Allah a cikin halittarsa, cewa yawancin mutane ba sa yin imani.

5. Don Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu ruwan Ɗufana ba irin sauran ruwaye ne da suka saba gani ba, sai ya fara ɓuɓɓugo da shi daga tanderun gurasa, watau inda ba a taɓa tsammanin za a ga ruwa yana ɓuɓɓugowa ba, watau daga cikin wuta, kafin kuma daga bisani Allah ya umarci sama ta kece da ruwa kamar da bakin ƙwarya, ƙasa kuma ta ɓarke da ɓulɓulo ruwa ta koʼina.

6. Ana son fara abubuwa da sunan Allah, kamar hawan abin hawa, irin jirgin ruwa ko na sama ko mota ko wata dabba.

7. Kusanci ko dangantaka da mutanen kirki ba za su amfani wanda bai yi imani ba.

8. Duk wasu sabubba na duniya komai girmansu ba za su amfani mai saɓon Allah ba idan Allah ya yi nufin yi masa uƙuba.

Suratu Hud (36-44)

وَأُوحِيَ إِلَىٰ نُوحٍ أَنَّهُۥ لَن يُؤۡمِنَ مِن قَوۡمِكَ إِلَّا مَن قَدۡ ءَامَنَ فَلَا تَبۡتَئِسۡ بِمَا كَانُواْ يَفۡعَلُونَ ٣٦ وَٱصۡنَعِ ٱلۡفُلۡكَ بِأَعۡيُنِنَا وَوَحۡيِنَا وَلَا تُخَٰطِبۡنِي فِي ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْۚ إِنَّهُم مُّغۡرَقُونَ ٣٧ وَيَصۡنَعُ ٱلۡفُلۡكَ وَكُلَّمَا مَرَّ عَلَيۡهِ مَلَأٞ مِّن قَوۡمِهِۦ سَخِرُواْ مِنۡهُۚ قَالَ إِن تَسۡخَرُواْ مِنَّا فَإِنَّا نَسۡخَرُ مِنكُمۡ كَمَا تَسۡخَرُونَ ٣٨ فَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَ مَن يَأۡتِيهِ عَذَابٞ يُخۡزِيهِ وَيَحِلُّ عَلَيۡهِ عَذَابٞ مُّقِيمٌ ٣٩ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَمۡرُنَا وَفَارَ ٱلتَّنُّورُ قُلۡنَا ٱحۡمِلۡ فِيهَا مِن كُلّٖ زَوۡجَيۡنِ ٱثۡنَيۡنِ وَأَهۡلَكَ إِلَّا مَن سَبَقَ عَلَيۡهِ ٱلۡقَوۡلُ وَمَنۡ ءَامَنَۚ وَمَآ ءَامَنَ مَعَهُۥٓ إِلَّا قَلِيلٞ ٤٠ ۞وَقَالَ ٱرۡكَبُواْ فِيهَا بِسۡمِ ٱللَّهِ مَجۡرٖىٰهَا وَمُرۡسَىٰهَآۚ إِنَّ رَبِّي لَغَفُورٞ رَّحِيمٞ ٤١ وَهِيَ تَجۡرِي بِهِمۡ فِي مَوۡجٖ كَٱلۡجِبَالِ وَنَادَىٰ نُوحٌ ٱبۡنَهُۥ وَكَانَ فِي مَعۡزِلٖ يَٰبُنَيَّ ٱرۡكَب مَّعَنَا وَلَا تَكُن مَّعَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٤٢ قَالَ سَـَٔاوِيٓ إِلَىٰ جَبَلٖ يَعۡصِمُنِي مِنَ ٱلۡمَآءِۚ قَالَ لَا عَاصِمَ ٱلۡيَوۡمَ مِنۡ أَمۡرِ ٱللَّهِ إِلَّا مَن رَّحِمَۚ وَحَالَ بَيۡنَهُمَا ٱلۡمَوۡجُ فَكَانَ مِنَ ٱلۡمُغۡرَقِينَ ٤٣ وَقِيلَ يَٰٓأَرۡضُ ٱبۡلَعِي مَآءَكِ وَيَٰسَمَآءُ أَقۡلِعِي وَغِيضَ ٱلۡمَآءُ وَقُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ وَٱسۡتَوَتۡ عَلَى ٱلۡجُودِيِّۖ وَقِيلَ بُعۡدٗا لِّلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٤

36. Aka kuma yi wa Nuhu wahayi cewa: “Ba wanda zai yi imani daga mutanenka sai waɗanda suka riga suka yi. To kada ka yi baƙin ciki game da abin da suke aikatawa.

37. “Ka kuma sassaƙa jirgin ruwa a kan idanunmu da koyarwarmu. Kada kuma ka yi Mini maganar komai game da kafirai. Lalle su nutsar da su za a yi.”

38. Ya kuma riƙa sassaƙa jirgin, duk sanda kuma wasu manya daga mutanensa suka wuce ta wajensa sai su riƙa yi masa ba’a. Ya ce: “Idan kun yi mana ba’a, to lalle mu ma fa (wata rana) za mu yi muku ba’ar kamar yadda kuke mana (yanzu).

39. “To ba da daɗewa ba za ku san wanda azaba mai kunyatarwa za ta zo masa, kuma wata azaba madawwamiya ta sauka a kansa.”

40. Har dai zuwa lokacin da umarninmu ya zo, kuma tanderu ya ɓuɓɓugo da ruwa, Muka ce: “Ka ɗauki ma’aurata bibbiyu daga kowace (halitta) a cikinsa (jirgin) haɗe da iyalanka in ban da wanda maganar (halakar da shi) ta gabata a kansa, kuma (ka ɗauki) waɗanda suka yi imani.” Ba kuwa waɗanda suka yi imani da shi sai ‘yan tsirari.

41. Ya kuma ce: “Ku shiga cikinsa, da sunan Allah ne tafiyarsa da kuma tsayawarsa. Lalle Ubangijina Mai gafara ne, Mai rahama.”

42. Shi kuma (jirgin) yana tafiya da su cikin raƙuman ruwa kamar duwatsu, Nuhu kuwa sai ya kirawo ɗansa alhalin ya kasance a ware waje ɗaya (ya ce): “Kai ɗana, ka hawo mana tare da mu, kada ka zama tare da kafirai.”

43. (Ɗan) ya ce: "Ai zan fake a wani dutse wanda zai kare ni daga ruwan." (Annabi Nuhu) ya ce: "Yau kam babu mai kariya daga alʾamarin Allah sai dai wanda Ya yi wa rahama kawai." Sai raƙumin ruwa ya shiga tsakaninsu, ya zamanto cikin waɗanda aka nutsar (a cikin ruwa).

44. Aka ce: "Ke ƙasa, ki haɗiye ruwanki, ke kuma sama ki riƙe ruwanki, aka kuwa ƙafar da ruwan, kuma aka gama alʾamarin, (jirgin) kuma ya tsaya a kan (dutsen) *Judi*; aka kuma ce: Halaka ta tabbata ga mutane azzalumai."
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa, Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi iya bakin ƙoƙarinsa wajen yi wa mutanensa nasiha, to amma sun ci gaba da yi masa taurin kai da izgili; kaɗan ne ƙwarai suka yi imani, Allah kuma ya sanar da shi cewa, bayan waɗannan ʻyan kaɗan da suka yi imani da shi babu sauran waɗanda za su ƙara yin imani nan gaba, don haka kada ya yi baƙin ciki da abin da suke aikatawa, domin babu abin da ya rage musu sai lokacin saukar azabar Allah a kansu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya sassaƙa jirgin ruwa ƙarƙashin kulawarsa da koyarwarsa, ya kuma umarce shi da kada ya kuskura ya nema wa kafirai wani jinkirin azaba domin Allah ya riga ya yanke musu hukuncin nutsarwa a cikin ruwan Ɗufana.

To Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya amsa umarnin Allah, ya fara sassaƙa jirgin ruwa, amma kuma mutanensa ba su ƙyale shi ba. Duk saʾadda manyansu suka wuce ta wajensa suka gan shi yana sassaƙar jirgin, sai su riƙa yi masa izgili suna tsokanar sa, har ma suna ganin ya zautu ne, domin me ya kai shi ga sassaƙa jirgin ruwa a garin da ba su da kogi ko ƙoramar da za a shiga da jirgi? Da abin ya ci gaba ba ƙaƙƙautawa sai ya faɗa musu cewa, idan yau suna yi masa izgilin wannan aikin da yake yi na sassaƙa, to ba da jimawa ba shi ma tare da jamaʾarsa za su yi musu izgili sakamakon abin da zai faru gare su. Kuma idan yau ba su gane dalilin sassaƙawar ba, to nan gaba za su ga wane ne wanda azaba za ta auka masa a nan duniya ta wulaƙanta shi ya kunyata, sannan kuma a lahira ya gamu da wata azaba marar yankewa.Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kammala sassaƙa jirgin ruwa, daga nan sai umarnin Allah ya zo na halakar su, sai kuma ruwa ya fara ɓuɓɓugowa da ƙarfi daga tanderun da suke gasa gurasa, daga nan ruwan Ɗufana ya ɓarke ya fara ambaliya, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya ɗauki aure biyu-biyu daga kowane jinsi na halittu masu rai tare da iyalansa a cikin wannan jirgi, in ban da wanda maganar halakarwa ta tabbata a kansa cewa ruwa zai cinye shi, watau ɗansa da matarsa, ya kuma ɗauki duk wanda ya yi imani da shi daga cikin mutanensa, waɗanda ʻyan kaɗan ne suka yi imani da shi duk tsawon lokacin da ya share a cikinsu yana yi musu waʾazi, watau shekara ɗari tara da hamsin.Sai ya umarci iyalansa da waɗanda suka yi imani daga cikin mutanensa da su hau wannan jirgin, da sunan Allah ne zai gudana a kan ruwa, kuma da sunansa ne zai tsaya. Lalle Allah Ubangijin Annabi Nuhu, mai gafara ne ga bayinsa da suka tuba, kuma mai jin ƙai ne gare su, don haka ne ma ya hore musu abin hawa da suka kuɓuta da shi daga halaka tare da sauran jinsunan halittu daban-daban.To yayin da jirgin ruwan yake tsakiyar tafiya da waɗanda ke cikinsa a tsakiyar raƙuman ruwa masu kamar duwatsu, sai tausayi na uba ya kama Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya kirawo ɗansa kafiri, wanda yake a ware waje guda ya ƙi bin babansa Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa da suka yi imani da shi. Nuhu ya ce masa: "Ya kai ɗan ɗana, zo ka hau jirgin ruwa tare da mu don kai ma ka tsira daga nutsewa cikin ruwa, kada ka zamo cikin kafirai waɗanda ruwa zai halaka su, sai ku halaka tare." Sai kawai ɗan ya ce masa, ai shi zai fake ne a ƙololuwar dutse inda ruwa ba zai kai gare shi ba. Sai Annabi Nuhu ya ce masa, a yau fa babu wani mai bayar da kariya daga azabar Allah sai wanda Allah ya yi wa rahamarsa kawai. Suna cikin haka sai kawai raƙumin ruwa ya shiga tsakaninsu, nan take kuma ɗan nasa ya tabbata cikin waɗanda ruwa ya cinye saboda kafircinsa.Daga ƙarshe sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci ƙasa ta tsotse ruwanta ita ma sama ya umarce ta da ta riƙe ruwanta ya daina zubowa. Ruwa ya yi ta ja da baya har ya ƙafe, ƙasa ta bushe, Allah ya halaka kafirai, jirgin

ruwan nan kuma ya tsaya a kan dutsen *Judi*, aka kuma ce wa waɗannan halakakkun kafiran, nisan rahama da halaka sun tabbata ga mutane kafirai masu ƙetare iyakokin Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawa ba su da ikon ceton wani kafiri ko da kuwa cikin ‘ya’yansu ne.

2. Ba ya halatta ga mutum ya roƙi Allah abin da ya saɓa wa sunnarsa da take gudana cikin halittarsa, ko ya roƙe shi abin da yake haramun ne.

3. Annabawa suna iya yin ijtihadi su yi kuskure, daga bisani Allah ya sanar da su kuskurensu kuma ya yafe musu shi.

4. Ba a gadon zama mutumin kirki; da kuwa ana gadon sa to da ba a samu mutumin banza ba a bayan ƙasa, domin dukkaninmu daga Annabi Adamu muke, kuma da sauran ‘ya’yan Annabi Nuhu da suka tsira a jirgin ruwa da dukkansu sun gaji zamantowa muminai, mutanen kirki.

5. Allah yana saka wa mutane a duniya da lahira ne da imaninsu da ayyukansu, ba da nasabarsu ko dangantakarsu ba. Don haka duk wanda yake ruɗuwa da nasabarsa, ya ƙi yin aiki na ƙwarai, wannan jahili ne bai san hukuncin Allah da Manzonsa ba.

6. Dangantakar mutane ta addini ta fi dangantakarsu ta jini.

7. Mutum yana iya roƙon Allah wani abu amma rashin amsa masa shi ne alheri gare shi, amma bai sani ba.

8. Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai da ya fara roƙon gafarar Allah sannan ya roƙi rahamarsa, domin idan ya gafarta masa to ya samu yardarsa, idan ya samu yardarsa sannan ne ya cancanci samun rahamarsa.

9. Tsoron Allah da kiyaye dokokinsa su ne suke haifar da cin nasara a rayuwa da kyakkyawan ƙarshe.

10. Alƙur’ani mu’ujiza ce daga Allah, domin ya ƙunshi labarukan gaibu na annabawa da al'ummunsu da ba zai yiwu Annabi ya san su ba tare da wahayi ba.

Suratu Hud (45-49)

وَنَادَىٰ نُوحٞ رَّبَّهُۥ فَقَالَ رَبِّ إِنَّ ٱبۡنِي مِنۡ أَهۡلِي وَإِنَّ وَعۡدَكَ ٱلۡحَقُّ وَأَنتَ أَحۡكَمُ ٱلۡحَٰكِمِينَ ٤٥ قَالَ يَٰنُوحُ إِنَّهُۥ لَيۡسَ مِنۡ أَهۡلِكَۖ إِنَّهُۥ عَمَلٌ غَيۡرُ صَٰلِحٖۖ فَلَا تَسۡـَٔلۡنِ مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٌۖ إِنِّيٓ أَعِظُكَ أَن تَكُونَ مِنَ ٱلۡجَٰهِلِينَ ٤٦ قَالَ رَبِّ إِنِّيٓ أَعُوذُ بِكَ أَنۡ أَسۡـَٔلَكَ مَا لَيۡسَ لِي بِهِۦ عِلۡمٞۖ وَإِلَّا تَغۡفِرۡ لِي وَتَرۡحَمۡنِيٓ أَكُن مِّنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٤٧ قِيلَ يَٰنُوحُ ٱهۡبِطۡ بِسَلَٰمٖ مِّنَّا وَبَرَكَٰتٍ عَلَيۡكَ وَعَلَىٰٓ أُمَمٖ مِّمَّن مَّعَكَۚ وَأُمَمٞ سَنُمَتِّعُهُمۡ ثُمَّ يَمَسُّهُم مِّنَّا عَذَابٌ أَلِيمٞ ٤٨ تِلۡكَ مِنۡ أَنۢبَآءِ ٱلۡغَيۡبِ نُوحِيهَآ إِلَيۡكَۖ مَا كُنتَ تَعۡلَمُهَآ أَنتَ وَلَا قَوۡمُكَ مِن قَبۡلِ هَٰذَاۛ فَٱصۡبِرۡۖ إِنَّ ٱلۡعَٰقِبَةَ لِلۡمُتَّقِينَ ٤٩

45. Nuhu kuma ya kira Ubangijinsa sai ya ce: “Ya Ubangijina, lalle ɗana yana daga iyalina, lalle kuma alƙawarinka gaskiya ne, kuma Kai ne Ka fi masu hukunci iya hukunci.”

46. (Allah) Ya ce: Ya Nuhu, lalle shi ba ya daga cikin iyalinka, lalle shi aiki ne marar kyau; to kada ka ƙara tambaya Ta abin da ba ka da sani a kansa; lalle Ni Ina gargaɗin ka da kada ka zamanto cikin jahilai.

47. Ya ce: “Ya Ubangijina, lalle ni ina neman tsarinka a kan in tambaye Ka abin da ba ni da sani a kansa, idan kuwa ba Ka yafe mini ba, Ka kuma ji ƙai na, to zan zamo cikin asararru.”

48. Aka ce: Ya Nuhu, ka sauka cikin aminci daga gare Mu da albarka a gare ka da kuma ga alʾummun da suke tare da kai. Wasu alʾummun kuma za Mu jiyar da su daɗî, sannan kuma azaba mai raɗàdî daga gare Mu ta same su.

49. Waɗannan suna daga labaran gaibu da muke yi maka wahayinsu, don kai da mutanenka ba ku san su ba kafin wannan (labarin); sai ka yi haƙuri; haƙiƙa kyakkyawan ƙarshe yana ga masu taƙawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana cewa, Annabi Nuhu ya kira Ubangijinsa yana gaya masa cewa, ɗansa mai halaka, shi ma yana cikin iyalansa, ga shi kuma ya yi masa alƙawarin tserar masa da iyalansa, kuma alƙawarin Allah gaskiya ne ba ya saɓawa, ya kuma fi kowa yin hukunci na adalci.Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar masa da martani cewa, wannan yaron ba ya cikin iyalansa, dalili kuwa shi ba mutumin ƙwarai ne ba domin kafiri ne, shi kuma Allah ya yi masa alƙawarin tserar da muminai ne kaɗai, don haka wannan roƙon ma da Annabi Nuhu ya yi bai dace ba, don haka Allah ya gargaɗe shi da kada ya sake roƙon abin da ba ya da wani ilimi a kansa, kada ya kuskura ya zama daga cikin jahilai waɗanda ba su san mene ne ya kamata su roƙa, mene ne kuma bai kamata su roƙa ba.Daga nan sai jikin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi sanyi ya dawo yana neman tsari da Allah a kan kada ya sake roƙon sa abin da ba shi da wani ilimi a kansa, kuma ya tabbatar da cewa idan har Allah bai gafarta masa wannan kuskuren da ya yi ba, ya kuma ji ƙan sa da rahamarsa, to zai zamanto cikin waɗanda suka yi asarar rabonsu na lahira.Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce da Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sauka daga jirgin ruwan cikin aminci da kwanciyar hankali da kuma niʾimomi masu yawa gare shi da kuma al'ummun da suke tare da shi, don su ci gaba da hayayyafa a bayan ƙasa har a samu wasu al'ummun da za su zo su sami ababen more rayuwa iri-iri. To amma kuma wasu daga cikinsu za su kafirce wa Allah su kuma butulce wa niʾimominsa, sai Allah ya ƙyale su su ɗan ji daɗî kaɗan a rayuwarsu ta duniya, amma in sun mutu za su haɗu da azabar Allah mai tsanani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, wannan labari da ya ba shi na Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana daga cikin labaran gaibu ne, wanda shi Annabi (ﷺ) da mutanensa duk ba su san shi ba, saboda Annabi (ﷺ) tun kafin ma a aiko shi mutum ne ummiyyi ba ya rubutu ba ya karanta rubutu, ballantana a zarge shi da ya karanto ne a littafan Yahudu da Nasara. Hakanan su ma mutanensa Ƙuraishawa ummiyai ne ba su iya rubutu da karatu ba, kuma ba su da wata alaƙa da maʾabota littafi ballantana su sanar da su wani labari irin wannan. To amma ga shi yanzu Allah ya yi masa wahayin sa, don haka ya umarce shi da ya yi haƙuri a kan ƙaryata shi da cutarwar da mutanensa suke yi masa, kamar yadda Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi haƙuri. Lalle kuma nasara da galaba suna tare da masu kiyaye dokokin Allah, masu aikata abin da ya umarce su, su kuma bar abin da ya hane su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Farkon daʾawar annabawa ita ce kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai ba tare da an haɗa shi da abokin tarayya ba.

2. Nisantar mai waʾazi daga abin hannun waɗanda yake yi wa waʾazi yana taimakawa wajen tasirin waʾazinsa.

3. Fahimtar gaskiya da karɓar ta alama ce ta aiki da hankali.

4. Neman gafarar Allah da tuba daga aikata zunubbai su ne hanyar samun arziki daga Allah.

5. Godiya ga ni'imomin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanya ni'imomin su ƙaru.

Suratu Hud (50-52)

وَإِلَىٰ عَادٍ أَخَاهُمْ هُودًا ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥٓ ۖ إِنْ أَنتُمْ إِلَّا مُفْتَرُونَ ﴿٥٠﴾ يَٰقَوْمِ لَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ أَجْرًا ۖ إِنْ أَجْرِىَ إِلَّا عَلَى ٱلَّذِى فَطَرَنِى ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿٥١﴾ وَيَٰقَوْمِ ٱسْتَغْفِرُوا۟ رَبَّكُمْ ثُمَّ تُوبُوٓا۟ إِلَيْهِ يُرْسِلِ ٱلسَّمَآءَ عَلَيْكُم مِّدْرَارًا وَيَزِدْكُمْ قُوَّةً إِلَىٰ قُوَّتِكُمْ وَلَا تَتَوَلَّوْا۟ مُجْرِمِينَ ﴿٥٢﴾

50. Kuma (Mun aiko wa) Adawa ɗan'uwansu Hudu, ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta da gaskiya sai shi; ku ba wasu ne ba face masu ƙaga wa (Allah) ƙarya.

51. "Ya ku mutanena, ba na tambayar ku wani lada game da shi (wannan saƙo); ladana dai yana ga wanda ya ƙagi halittata. Yanzu ba za ku hankalta ba?

52. "Kuma ya ku mutanena, ku nemi gafarar Ubangijinku sannan ku tuba gare Shi, zai sauko muku da mamakon ruwan sama, zai kuma ƙara muku ƙarfi a kan ƙarfinku, kada kuma ku ba da baya kuna masu aikata laifi."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin Annabi Hudu ne, wanda ya aika shi zuwa ga Adawa. (Bayanin ƙabilun Adawa ya gabata cikin *Suratul A'arafi* aya ta 65).Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kirawo mutanensa zuwa ga bautar Allah shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba, ya nuna musu cewa, iƙirarinsu na cewa akwai wani abin bauta wa ban da Allah ƙarya ce kawai suke yi. Ya tabbatar musu cewa, ba ya buƙatar wani abu daga dukiyarsu a kan wannan waʾazi da yake yi musu, ladansa yana wajen Allah ne shi kaɗai, don haka me zai hana su hankalta da abin da yake faɗa musu su yi imani da shi?Sannan ya neme su da su roƙi Allah gafara su kuma tuba su daina aikata zunubbai, musamman yin shirka da Allah, idan suka yi haka zai saka musu ta hanyar saukar musu da mamakon ruwan sama, wanda zai ba su damar samun amfanin gona mai yawa, kuma ya ƙara musu ƙarfi da ɗaukaka a kan wanda suke da shi, ya yalwata musu 'ya'yansu da dukiyoyinsu. Ya kuma gargaɗe su da kada su kuskura su bijire wa kiransa sai su zama masu aikata manyan laifuka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu wani annabi da Allah ya aiko ba tare da ya ba shi hujjoji bayyanannu masu tabbatar da gaskiyar annabcinsa ba. Amma duk da haka mutanen Annabi Hudu suke ƙaryar cewa bai zo musu da wata hujja ba.

2. Daga cikin hanyoyin da mushirikai suke bi wajen hana mutane yarda da manzanni shi ne tuhumar su da taɓin hankali.
3. Annabi Hudu ya mayar musu da martani wanda ya ƙunshi abubuwa kamar haka:
• Nesanta kansa daga shirkar da suke yi da Allah.
• Shaidar da Allah a kan haka. Wannan kuwa yana nuna yadda ya gamsu da cewa yana da hujja daga gare shi.
• Shaidar da su a kan hakan, yana tabbatar da cewa shi bai damu da kurin da suke yi masa ba na cewa gumakansu za su iya cutar da shi.
• Don haka ne ma ya nemi cewa su haɗu su da gumakan nasu gaba ɗaya su cutar da shi in suna da iko a kan hakan.

4. Duk wanda imani da dogaro ga Allah ya cika masa zuciya, to tsoron wanin Allah ba zai shige ta ba.

5. Kowa da komai a hannun Allah suke, babu mai iya motsi sai da yardarsa da izininsa.

6. Ayyukan Allah duka suna gudana ne bisa hikimarsa da adalcinsa da falalarsa, don haka hanyarsa ce miƙaƙƙiya, duk hanyar da ta saɓa wa tashi, to karkatacciyar hanya ce.

7. Allah ba shi da buƙatar komai wurin kowa, don haka yana iya kawar da duk wanda ya saɓa masa ya ƙi bin umarninsa, ya kawo wani gurbinsa ba tare da ya cutu da komai ba.

Suratu Hud (53-57)

قَالُواْ يَٰهُودُ مَا جِئۡتَنَا بِبَيِّنَةٖ وَمَا نَحۡنُ بِتَارِكِيٓ ءَالِهَتِنَا عَن قَوۡلِكَ وَمَا نَحۡنُ لَكَ بِمُؤۡمِنِينَ ٥٣ إِن نَّقُولُ إِلَّا ٱعۡتَرَىٰكَ بَعۡضُ ءَالِهَتِنَا بِسُوٓءٖۗ قَالَ إِنِّيٓ أُشۡهِدُ ٱللَّهَ
وَٱشۡهَدُوٓاْ أَنِّي بَرِيٓءٞ مِّمَّا تُشۡرِكُونَ ٥٤ مِن دُونِهِۦۖ فَكِيدُونِي جَمِيعٗا ثُمَّ لَا تُنظِرُونِ ٥٥ إِنِّي تَوَكَّلۡتُ عَلَى ٱللَّهِ رَبِّي وَرَبِّكُمۡۚ مَّا مِن دَآبَّةٍ إِلَّا هُوَ ءَاخِذُۢ بِنَاصِيَتِهَآۚ
إِنَّ رَبِّي عَلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٥٦ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقَدۡ أَبۡلَغۡتُكُم مَّآ أُرۡسِلۡتُ بِهِۦٓ إِلَيۡكُمۡۚ وَيَسۡتَخۡلِفُ رَبِّي قَوۡمًا غَيۡرَكُمۡ وَلَا تَضُرُّونَهُۥ شَيۡـٔاۚ إِنَّ رَبِّي عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٍ
حَفِيظٞ ٥٧

53. Suka ce: “Ya kai Hudu ba ka zo mana da wata hujja ba, kuma ba za mu bar abubuwan da muke bauta ba saboda maganarka, ba kuma za mu yi imani da kai ba.

54. “Ba abin da za mu faɗa sai dai kawai (mu ce) wasu abubuwan bautarmu ne suka sa maka taɓuwa.” Ya ce: “Ni lalle ina shaidar da Allah, ku ma kuma ku shaida cewa ni lalle ba ruwana da abin da kuke haɗa (Allah) da shi.

55. “Wanda ba Shi (Allah) ba; to sai ku shirya min makirci gaba ɗayanku, kar kuma ku saurara mini.

56. “Lalle ni na dogara ga Allah, Ubangijina kuma Ubangijinku. Babu wata dabba face Shi ne Yake riƙe da makwarkwaɗarta. Lalle Ubangijina a kan tafarki madaidaici Yake.

57. “To idan kuka ba da baya, haƙiƙa na isar muku abin da aka aiko ni da shi zuwa gare ku. Kuma Ubangijina zai iya musanya wasu mutanen ba ku ba, kuma ba za ku cutar da Shi da komai ba. Lalle Ubangijina Mai kula da komai ne.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana irin mummunan martani da mutanen Annabi Hudu suka mayar masa bayan ya kirawo su da tattausar murya tare da jan hankalinsu zuwa ga bautar Allah shi kaɗai da guje wa shirka. Wasu kausasan maganganu uku suka gaya masa:
Na farko: Suka ce wai bai kawo musu wata hujja ba a kan daʾawarsa ta manzanci.
Na biyu: Suka nuna masa cewa, sam-sam ba za su taɓa barin bautar gumakansu ba saboda waʾazinsa. Wannan yana nuna sun riga sun ɗauki matsayi na kafewa a kan shirkarsu, ba suna neman gaskiya ba ne.
Na uku: Suka tabbatar masa cewa ba za su taɓa yin imani da shi ba. Wannan yana ƙara nuna kafewarsu a kan kafirci.Bugu da ƙari kuma suka ci gaba da tuhumar sa da taɓin hankali, suna ganin wai wasu gumakansu ne suka yi fushi da shi har suka haukatar da shi saboda yana sukan su da aibata su da hana a bauta musu. To amma sai Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sake tausasa harshensa wajen ba su amsar waɗannan maganganun, yana cewa, shi kam ya sanya Allah a matsayin mai yi masa shaida, su ma su shaida cewa ya nisanta kansa daga bautar abin da suke bauta wa ba Allah ba. Sannan ya ƙalubalance su

da, su shirya masa makirci gaba ɗayansu, kada kuma su saurara masa. Ya tabbatar musu da cewa, shi kam da Allah kaɗai ya dogara ba da wani ba, shi ne Ubangijinsa mai gudanar da lamuran rayuwarsa kuma shi ne Ubangijinsu, babu wani abu mai tafiya a kan ƙasa face yana ƙarƙashin mulkin Allah ne, shi yake riƙe da makwarkwaɗarsa yana sarrafa shi yadda ya ga dama. Don haka Ubangijinsa yana kan hanya miƙaƙƙiya, wadda take cike da adalci, don haka ba zai taɓa ba su damar cutar da shi ba, domin shi ne a kan gaskiya su kuma a kan ɓata.Sannan ya nuna musu cewa, idan suka bijire wa kiransa, to fa shi tabbas ya isar musu da saƙon da aka aiko shi da shi, don haka hujja ta tabbata a kansu, Allah kuwa yana iya hallakar da su gaba ɗayansu, ya zo da wasu mutanen a madadinsu, kuma ba za su cuci Allah da komai ba don sun ƙaryata shi sun bi son zuciyarsu. Allah kuma shi ne mai kula da komai, shi ne mai kare Annabinsa Hudu babu mai iya cutar da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Waɗanda suka yi imani da Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ya nufe su da rahama, don haka ya nufe su da yin imani ya kuma ba su damar aiki nagari, wanda a dalilinsa Allah ya tserar da su daga azaba mai tsanani.

2. Duk da cewa Adawa sun ƙaryata Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi kaɗai ne, to amma Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce sun saɓa wa manzanninsa. Wannan yana nufin ƙaryata manzo ɗaya tamkar ƙaryata su ne gaba ɗayansu.

3. Babu wani uzuri ga mabiyan da za su bi shugabanninsu a kan ɓata suna sane, fushin Allah idan ya zo zai haɗa da su ne gaba ɗaya.

Suratu Hud (58-60)

وَلَمَّا جَآءَ أَمۡرُنَا نَجَّيۡنَا هُودٗا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ بِرَحۡمَةٖ مِّنَّا وَنَجَّيۡنَٰهُم مِّنۡ عَذَابٍ غَلِيظٖ ٥٨ وَتِلۡكَ عَادٞۖ جَحَدُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ وَعَصَوۡاْ رُسُلَهُۥ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَمۡرَ كُلِّ جَبَّارٍ عَنِيدٖ ٥٩ وَأُتۡبِعُواْ فِي هَٰذِهِ ٱلدُّنۡيَا لَعۡنَةٗ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ أَلَآ إِنَّ عَادٗا كَفَرُواْ رَبَّهُمۡۗ أَلَا بُعۡدٗا لِّعَادٖ قَوۡمِ هُودٖ ٦٠

58. Lokacin kuwa da umarninmu ya zo sai Muka tserar da Hudu shi da waɗanda suka ba da gaskiya da shi, saboda wata rahama daga gare mu, Muka kuma tserar da su daga azaba mai gwaɓi.

59. Waɗancan kuwa su ne Adawa, da suka musanta ayoyin Ubangijinsu, suka kuma saɓa wa manzanninsa, kuma suka bi umarnin duk wani mai girman kai taƙadari.

60. Aka kuma biyar musu da laʾana a duniya, haka kuma a ranar alƙiyama. Ku saurara! Lalle Adawa kam sun kafirce wa Ubangijinsu. Ku saurara! Halaka ta tabbata ga Adawa mutanen Hudu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, yayin da mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka dage a kan kafircinsu da ƙaryata shi, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yanke hukuncin hallakar da su, ya kuma tserar da Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka yi imani da shi. Sai ya aiko musu da wata bakarariar iska wadda ta riƙa rugurguza duk wani abu da ta biyo ta kansa da izinin Allah cikin tsawon kwana bakwai da yini takwas a jere, ta zubar da Adawa a ƙasa a marmace kamar kututturan dabinai da aka rarake, kamar yadda ya zo a cikin *Suratul Ƙamari*, aya ta 18-20.Allah ya tserar da Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka ba da gaskiya da shi daga wata mummunar azaba mai gwaɓi domin rahamar Allah gare shi da jamaʾarsa.Allah kuma ya bayyana dalilan da suka jawo musu wannan azaba, watau kafirce wa ayoyinsa da

suka yi, kuma suka saɓa wa Manzonsa Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), suka yi biyayya ga umarnin duk wani azzalumi mai girman kai kangararre maƙiyin gaskiya. Wannan kuma ya sa laʾana ta yi ta bin su a duniya. Watau duk wani mutumin kirki da ya ji irin mummunan labarinsu sai ya laʾance su, sannan kuma a ranar alƙiyama malaʾiku su ci gaba da laʾantar su. Haƙiƙa Adawa sun kafirce wa Ubangijinsu, sun butulce wa niʾimomin da ya yi musu, suka ƙaryata Manzonsa Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Don haka nesantar rahamar Allah ta tabbata ga Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta da nesantar shirka, shi ne farkon kiran duk manzannin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Yana daga cikin dalilan kaɗaitakar Allah da bauta zamantowarsa shi ne mahalicci wanda ya halicci kowa da komai.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne ya ba wa ɗanʾadam damar ya raya ƙasa da gine-gine da sanaʾoʾin da rayuwar ɗanʾadam take buƙata, amma bisa tsarin da ya ɗora shi a kai na bauta masa shi kaɗai ba tare da ya haɗa shi da abokin tarayya ba.

4. Duk wanda ya lizimci istigfari da tuba zuwa ga Allah zai samu kusanci da shi kuma addu'arsa za ta zama karɓaɓɓa a wurinsa.

5. Duk wani annabi da Allah ya aiko yakan kasance sananne a wurin mutanensa da kyawawan halaye da ɗabiʾu tun kafin a ba shi annabci.

6. Wajibi a kan mai kira zuwa ga Allah ya kasance a kan hujja bayyananna game da abin da yake kiran mutane a kansa, watau ya tabbatar da masʾalar da zai yi magana a kanta kafin ya ce komai a kai.

7. Mumini yana sane da cewa alherin shiriya da nagarta da tsoron Allah da yake rayuwa a cikinsu duk baiwa ce daga Allah da rahamarsa.
8. Wanda zai kirawo ka zuwa saɓon Allah ka sani ba zai iya kare ka daga azabar Allah ba.

9. Dukkan annabawa suna jin tsoron saɓa wa Allah, kada ya kama su da laifin saɓa masa, don haka duk wanda ya yi daʾawar cewa akwai wani matsayi da wani zai kai wanda ɗaʾar Allah da saɓa masa za su zama daidai a wurinsa, to babu shakka wannan ya ɓace daga kan tafarkin annabawa baki ɗaya.

10. Duk wanda ya yarda ya saɓa wa Allah don ya faranta wa wani rai, to haƙiƙa wannan da ya bi shi ya saki hanyar Allah ba komai zai ƙara masa ba sai taɓewa da hasara duniya da lahira.

Suratu Hud (61-65)

*وَإِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمْ صَٰلِحًا ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥ ۖ هُوَ أَنشَأَكُم مِّنَ ٱلْأَرْضِ وَٱسْتَعْمَرَكُمْ فِيهَا فَٱسْتَغْفِرُوهُ ثُمَّ تُوبُوٓا۟ إِلَيْهِ ۚ إِنَّ رَبِّى قَرِيبٌ مُّجِيبٌ ﴿٦١﴾ قَالُوا۟ يَٰصَٰلِحُ قَدْ كُنتَ فِينَا مَرْجُوًّا قَبْلَ هَٰذَآ ۖ أَتَنْهَىٰنَآ أَن نَّعْبُدَ مَا يَعْبُدُ ءَابَآؤُنَا وَإِنَّنَا لَفِى شَكٍّ مِّمَّا تَدْعُونَآ إِلَيْهِ مُرِيبٍ ﴿٦٢﴾ قَالَ يَٰقَوْمِ أَرَءَيْتُمْ إِن كُنتُ عَلَىٰ بَيِّنَةٍ مِّن رَّبِّى وَءَاتَىٰنِى مِنْهُ رَحْمَةً فَمَن يَنصُرُنِى مِنَ ٱللَّهِ إِنْ عَصَيْتُهُۥ ۖ فَمَا تَزِيدُونَنِى غَيْرَ تَخْسِيرٍ ﴿٦٣﴾ وَيَٰقَوْمِ هَٰذِهِۦ نَاقَةُ ٱللَّهِ لَكُمْ

ءَايَةً ۖ فَذَرُوهَا تَأۡكُلۡ فِيٓ أَرۡضِ ٱللَّهِ وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوٓءٖ فَيَأۡخُذَكُمۡ عَذَابٞ قَرِيبٞ ٦٤ فَعَقَرُوهَا فَقَالَ تَمَتَّعُواْ فِي دَارِكُمۡ ثَلَٰثَةَ أَيَّامٖۖ ذَٰلِكَ وَعۡدٌ غَيۡرُ مَكۡذُوبٖ ٦٥

61. Haka kuma Muka aiko wa Samudawa ɗan'uwansu Salihu. Ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta ba shi ba; Shi ne Ya halicce ku daga ƙasa, Ya kuma ba ku damar ku raya ta; to ku nemi gafararsa sannan ku tuba gare Shi. Lalle Ubangijina Makusanci ne, Mai amsawa."

62. Suka ce: "Ya Salihu, haƙiƙa a da ka kasance a cikinmu abin yi wa (kyakkyawan) fata kafin (ka zo mana da) wannan; yanzu ka riƙa hana mu mu bauta wa abin da iyayenmu suke bauta wa? Lalle mu kam tabbas muna matuƙar shakka game da abin da kake kiran mu gare shi."

63. Ya ce: "Ya ku mutanena, ku ba ni labari, yanzu idan na kasance a kan bayyananniyar hujja daga Ubangijina, Ya kuma ba ni rahama (ta annabci) to wa zai kare ni daga (azabar) Allah idan na saɓa masa? Don haka babu abin da za ku ƙara ni da shi in ban da taɓewa."

64. "Kuma ya ku mutanena, wannan fa taguwar Allah ce a gare ku, sai ku bar ta ta ci a ƙasar Allah, kada ku cutar da ita, sai azaba ta kusa-kusa ta afka muku."

65. Amma sai suka soke ta, sai ya ce (da su): "Ku ji dadî cikin gidajenku kwana uku (rak). Wannan alƙawari ne ba abin ƙaryatawa ba."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba mu labarin Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya aiko shi zuwa ga ƙabilun Samudawa, waɗanda suna daga cikin ƙabilun Larabawa. Sun rayu ne a garin *Al-Hijr*wanda ke tsakanin Madina da ƙasar Sham. Annabi Salihu ɗan'uwansu ne na jini, ya kirawo su zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, ya nuna musu ba su da wani abin bauta bisa cancanta sai Allah shi kaɗai, kuma shi ne ya halicce su daga ƙasa, domin kuwa shi ya halicci babansu Annabi Adamu, sannan ya saukar da su a bayan ƙasa, ya umarce su da su raya ta da bautar Allah ya kuma ba su damar noma ƙasa da gudanar da sauran sana'o'i da yin gine-gine a bayan ƙasa, don haka su nemi gafarar Allah game da shirkar da suka yi da Allah da kafirci da saɓon Allah, sannan su yi tuba na gaskiya gare shi. Lalle shi Ubangiji makusanci ne ga duk wanda ya tsarkake bauta gare shi, kuma mai karɓar addu'arsa ne.To da jin waɗannan kalamai daga Annabi Salihu sai suka nuna masa cewa, ba za su yarda da shi ba, domin a da suna yi masa kallon mutumin kirki, har ma suna masa fatan alheri, suna sa ran zai zama mai hankali kuma mai faɗa a ji, to amma yanzu da ya zo da waɗannan maganganu, mutuncinsa ya zube a idanunsu. Laifinsa kuwa shi ne, wai yaya zai hana su bauta wa abin da suka tarar da iyayensu suna bauta wa; wannan alama ce da ke nuna yana sukan iyayensu ne, don haka su lalle suna shakkar abin da yake kiran su gare shi na barin bautar gumakansu su dawo ga bautar Allah shi kaɗai, don haka su suna tababar gaskiyarsa, saboda haka ba za su yarda da shi ba.Sai Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya mayar musu da martani cewa, su faɗa masa, shin yanzu idan ya zamanto yana kan wata hujja bayyananna daga Ubangijinsa, sannan kuma Allah ya ba shi annabta daga wajensa, to shi ke nan sai ya yi watsi da wannan hujjar, ya watsar da annabcin da aka ba shi, ya dawo yana bin son zuciyarsu, shi ma ya amince da bautar wanin Allah? Ya kuma tambaye su, wane ne zai kare shi daga azabar Allah idan har ya watsar da isar da saƙon Allah gare su? Don haka ya tabbatar musu da cewa, wannan kira da suke yi masa ba abin da zai ƙara masa a wurin Allah in ban da taɓewa da asara ninki-ba-ninki.Mutanen Annabi Salihu sai suka ƙalubalance shi da cewa, sai ya fito musu da wata taguwa daga wani dutse domin ta zame masa hujjar da take tabbatar da gaskiyar annabcinsa. Allah kuma ya karɓa musu ya yarda zai fitar masa da taguwar amma a kan wasu sharuɗɗa uku da ya gindaya musu, kamar haka:Na farko: Su ƙyale ta ta yi kiwo a bayan ƙasa ta ci abin da take so.Na biyu: Ruwan da suke amfani da shi zai zama na tarayya ne tsakaninsu da ita, watau yau idan sun

ɗìbi ruwan sha, gobe kuma sai su bar wa wannan taguwar ta sha ita kaɗai.Na uku: Kada su kuskura su cutar da taguwar.Idan sun kiyaye waɗannan sharuɗɗa to za su zauna da wannan taguwa lafiya, idan kuwa suka kuskura suka karya wani sharaɗi daga cikin waɗannan sharuɗɗa to wata azaba ta kusa za ta auka musu.Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi musu wannan gargaɗi amma ba su ɗauki gargaɗinsa a bakin komai ba, don haka sai suka soke wannan taguwar, domin su tabbatar wa da mutane cewa Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) maƙaryaci ne. Ganin haka sai ya sanar da su cewa, su zauna a gidajensu su ji daɗi na tsawon kwana uku rak daga lokacin da suka soke taguwar, sannan azabar Allah za ta auka musu, kuma yana tabbatar musu da cewa wannan alƙawari ne ba na ƙaryatawa ba, kamar yadda su suke tsammani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuɓutar da Salihu da jama'arsa muminai da rahamarsa ne, ba wai don kawai ayyukansu na ƙwarai ba. Hakanan idan saboda ayyukansu ne, kuma su ne Allah ya kirawo da suna 'rahama', to su ɗin ma daga gare shi ne, domin shi ne ya datar da su ga aikata kyawawan ayyuka.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan nuna wa bayinsa ƙasaitacciyar Ƙudirarsa, da kuma bayyana cewa shi mai aikata abin da ya ga dama ne, don haka da ya tashi hallakar da Samudawa masu ji da ƙarfi da alfahari da girman jiki sai ya halaka su da iska, wadda take wata halitta ce marar nauyi kuma marar jiki da ake gani a taɓa.

3. Allah ya shafe Samudawa gaba ɗaya ya share samuwarsu daga bayan ƙasa kamar da ma can ba a taɓa halittar su a wuraren ba.

Suratu Hud (66-68)

فَلَمَّا جَآءَ أَمۡرُنَا نَجَّيۡنَا صَٰلِحٗا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ بِرَحۡمَةٖ مِّنَّا وَمِنۡ خِزۡيِ يَوۡمِئِذٍۗ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ ٱلۡقَوِيُّ ٱلۡعَزِيزُ ٦٦ وَأَخَذَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ ٱلصَّيۡحَةُ فَأَصۡبَحُواْ فِي دِيَٰرِهِمۡ جَٰثِمِينَ ٦٧ كَأَن لَّمۡ يَغۡنَوۡاْ فِيهَآۗ أَلَآ إِنَّ ثَمُودَاْ كَفَرُواْ رَبَّهُمۡۖ أَلَا بُعۡدٗا لِّثَمُودَ ٦٨

66. To lokacin da umarninmu ya zo sai Muka tserar da Salihu shi da waɗanda suka yi imani tare da shi saboda wata rahama daga gare mu, kuma (Muka tserar da su) daga kunyatar wannan rana. Lalle Ubangijinka Shi ne Mai ƙarfi Mabuwayi.

67. Kuma tsawa ta kama waɗanda suka yi zalunci, sai suka wayi gari cikin gidajensu a duddurƙushe (babu rai).

68. Kamar daɗai ba su taɓa zama a cikinsu ba (gidajen). Ku saurara! Lalle Samudawa kam sun kafirce wa Ubangijinsu. Ku saurara! Halaka ta tabbata ga Samudawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin yadda ya saukar wa Samudawa azabarsa yayin da suka saɓa wa umarnin Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka soke taguwar Allah. Allah ya bayyana cewa, yayin da umarninsa na halakar da su ya zo bayan ƙarewar wa'adin kwana uku da aka ba su, sai ya tserar da Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka yi imani tare da shi da rahamarsa, ya kuma kuɓutar da su daga wulaƙancin wannan ranar. Allah ya tabbatar wa Manzon Allah (ﷺ) cewa lalle Ubangijinsa shi ne ƙaƙƙarfa mabuwayi, babu wanda zai iya karawa da shi har ya yi rinjaye, don haka ne ya iya hallakar da Samudawa duk kuwa da ƙarfin da suke ji da shi.Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta nau'in hallakarwar da ya yi musu, watau ya aiko musu da wata tsawa mai tsananin gaske wadda nan da nan ta hallakar da su duk suka mutu saboda zaluncinsu da kafircinsu ga Allah

da ƙaryata Manzonsa Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai ga shi sun wayi gari cikin gidajensu a duddurƙushe duk ƙasa ta bice fuskokinsu babu mai sauran motsi, kai ka ce ba su taɓa rayuwa mai dadi a cikin gidajensu ba.Allah ya ƙara jaddada laifin da Samudawa suka yi har suka cancanci ya yi musu irin wannan halakarwar, watau sun kafirce masa ne, don haka nesanta daga rahamarsa ta tabbata gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mala'iku Allah ya ba su ikon rikiɗa zuwa ga halittar ɗan'adam, amma suna fitowa ne cikin kyakkyawar kama.

2. Sallama ita ce gaisuwar duk annabawan Allah da suka gabata, kuma ita ce gaisuwar mala'iku.

3. Gaggauta kawo wa baƙo liyafar abin ci ko na sha ba sai ya nema ba, yin haka shi ne karamci.

4. Kyautata wa baƙo ta hanyar kawo masa mafi daɗin abincin da ake da shi a gida.

5. Yana daga cikin karamci ga baƙo, mai gida ya yi masa hidima da kansa.

6. Idan baƙo ya ci abincin da aka kawo masa wannan yakan sanya nutsuwa a zuciyar masu gida da yarda da shi.

7. Wasu malamai sun kafa hujja da wannan ayar ta 71 a kan cewa, Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne wanda Allah ya umarci mahaifinsa Ibrahimu ya yanka ba Is'haƙa ba, domin shi ne zai haifar masa jika, watau Annabi Yaƙubu; to ta yaya kuma zai yi umarnin a yanka shi tun yana yaro ƙarami bai kai ga haifa masa jikan ba? Allah kuwa ba ya yin alƙawari ya saɓa. Don haka wannan ya tabbatar da cewa Isma'ila shi ne wanda aka ba da umarnin a yanka tun yana yaro.

8. Matar mutum tana cikin ahalinsa.

Suratu Hud (69-73)

وَلَقَدۡ جَآءَتۡ رُسُلُنَآ إِبۡرَٰهِيمَ بِٱلۡبُشۡرَىٰ قَالُواْ سَلَٰمٗاۖ قَالَ سَلَٰمٞۖ فَمَا لَبِثَ أَن جَآءَ بِعِجۡلٍ حَنِيذٖ ٦٩ فَلَمَّا رَءَآ أَيۡدِيَهُمۡ لَا تَصِلُ إِلَيۡهِ نَكِرَهُمۡ وَأَوۡجَسَ مِنۡهُمۡ خِيفَةٗۚ قَالُواْ لَا تَخَفۡ إِنَّآ أُرۡسِلۡنَآ إِلَىٰ قَوۡمِ لُوطٖ ٧٠ وَٱمۡرَأَتُهُۥ قَآئِمَةٞ فَضَحِكَتۡ فَبَشَّرۡنَٰهَا بِإِسۡحَٰقَ وَمِن وَرَآءِ إِسۡحَٰقَ يَعۡقُوبَ ٧١ قَالَتۡ يَٰوَيۡلَتَىٰٓ ءَأَلِدُ وَأَنَا۠ عَجُوزٞ وَهَٰذَا بَعۡلِي شَيۡخًاۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَيۡءٌ عَجِيبٞ ٧٢ قَالُوٓاْ أَتَعۡجَبِينَ مِنۡ أَمۡرِ ٱللَّهِۖ رَحۡمَتُ ٱللَّهِ وَبَرَكَٰتُهُۥ عَلَيۡكُمۡ أَهۡلَ ٱلۡبَيۡتِۚ إِنَّهُۥ حَمِيدٞ مَّجِيدٞ ٧٣

69. Haƙiƙa kuma mazanninmu sun zo wa Ibrahimu da albishir, suka ce: "Aminci (a gare ku)", ya ce: "Aminci (a gare ku kuma)." To bai zauna ba sai da ya kawo musu soyayyen ɗan maraƙi.

70. To lokacin da ya ga hannayensu ba sa isa gare shi (soyayyen ɗan maraƙin), sai ya shiga yin ɗari-ɗari da su, kuma ya ɓoye jin tsoronsu a zuciyarsa, suka ce: "Kar ka tsorata; mu an aiko mu ne zuwa ga mutanen Ludu."

71. Matarsa kuwa tana tsaye sai ta yi dariya, sai Muka yi mata albishir da Is'haƙa, bayan kuma Is'haƙa (sai) Yakubu.

72. Ta ce: "Kaicona! Yanzu zan iya haihuwa, ga ni tsohuwa kuma ga mijina nan ma tsoho? Lalle wannan abin mamaki ne!"

73. Suka ce: “Yanzu kya riƙa mamaki game da al’amarin Allah? Rahamar Allah da albarkarsa su tabbata a gare ku mutanen wannan gidan. Lalle shi (Allah) Sha-yabo ne Mai girma.”
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin wani ɓangare ne na ƙissar Annabi Ibrahimu da Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kuma ya dunƙule labarinsu wuri guda ne saboda manzancinsu ya kasance a zamani ɗaya ne. Haka kuma shi Annabi Luɗu ya yi imani ne ta hannun baffansa Annabi Ibrahimu. Allah ya zaɓe shi ya kuma aika shi Manzo zuwa ga mutanen alƙaryar Sadum a cikin ƙasar Sham, saboda wani ƙazamin aiki da suka shahara da shi, wanda a gabaninsu ba a taɓa samun mai aikata irinsa ba, wannan aikin kuwa shi ne zaike wa maza ta dubura. Annabi Luɗu ya duƙufa ga yi musu waʾazi amma sun bijire masa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nufi hallakar da su, don haka ya aiko malaʾiku don su cika aiki.Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yayin da malaʾikun nan suka tashi zuwa sai suka fara biyawa ta wurin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a siffar samari don su yi masa albishir da samun ɗa namiji da matarsa Sara da kuma samun jika annabi. Malaʾikun suka fara da yi masa sallama shi kuma ya amsa sallamarsu, nan take bai zauna ba sai ya shiga wajen iyalansa da sauri ya kawo musu liyafa ta gasasshen ɗan maraƙi, don yana tsammanin su mutane ne matafiya suka baƙunce shi.Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yayin da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ga hannayen baƙinsa ba sa isa kan naman da aka kawo musu, sai ya kasa gane manufarsu, tsoronsu kuma ya shige shi, to amma sai ya ɓoye tsoron a zuciyarsa bai nuna musu ba. To amma duk da haka sai malaʾikun suka fahimci halin da yake ciki, sai suka ce masa, kada ya ji tsoron su, su malaʾikun Allah ne, kuma ya aiko su ne zuwa ga mutanen Annabi Luɗu don su halaka su, saboda mummunan laifinsu ya tsananta sosai. A daidai lokacin kuma Saratu matar Annabi Ibrahimu tana tsaye bayan labule tana sauraren tattaunawar mijinta da baƙinsa malaʾiku, da jin cewa za a halakar da mutanen Annabi Luɗu, sai farin ciki ya ishe ta har ta fashe da dariya. Sai ita ma suka yi mata albishir na samun haihuwar ɗa namiji, watau Isʾhaƙa, shi ma kuma zai rayu ya girma har ya haifi ɗa Yaʾaƙubu, dukkaninsu kuma annabawa.Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da cewa, yayin da Saratu ta ji albishirin da aka yi mata na samun haihuwa, sai mamaki ya kama ta matuƙa, sai ta ka da baki ta ce musu, yanzu yaya zai yiwu a ce ta haihu ga ta tsohuwa mijinta ma tsoho? Ta ce babu shakka wannan abin mamaki ne. To amma sai malaʾikun suka amsa mata da cewa, yanzu yaya za ta riƙa mamakin Ƙudirar Allah da ikonsa? Ai ta san Allah mai iko ne a kan komai, kuma rahamarsa da albarkatunsa sun tabbata gare su, su mutanen gidan Annabi Ibrahimu. Lalle kuwa Allah abin yabo ne kuma mai girma.

An karɓo daga Kaʾabu ɗan Ujrah (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mun tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa: “Lalle Allah ya koya mana yadda za mu yi muku sallama, to amma yaya za mu yi muku salati ku Ahlul Baiti?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ku ce: “Ya Allah ka yi salati ga Muhammadu da kuma iyalan gidan Muhammadu, kamar yadda ka yi salati ga Ibrahimu da iyalan gidan Ibrahimu, lalle kai ne abin yabo mai girma. Ya Allah ka yi albarka ga Muhammadu da kuma iyalan gidan Muhammadu, kamar yadda ka yi albarka ga Ibrahimuu da iyalan gidan Ibrahimu, lalle kai ne abin yabo mai girma.” [Bukhari #3370 da Muslim #407]

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haƙurin Annabi Ibrahimu da tausayinsa ga al’ummarsa.

2. Idan azabar Allah ta riga ta zo wa mai saɓa masa to babu wanda ya isa ya mayar da ita.

3. Ya dace koyaushe a yi wa masu saɓon Allah fatan shiriya da rahama.

4. Idan ya kasance Annabi Ibrahimu badaɗayin Allah mai rahama mutum ne mai yawan tuba da komawa ga Allah, to me ya sa mu muke kasa bin hanyarsa ta tuba da komawa ga Allah?

Suratu Hud (74-76)

فَلَمَّا ذَهَبَ عَنْ إِبْرَٰهِيمَ ٱلرَّوْعُ وَجَآءَتْهُ ٱلْبُشْرَىٰ يُجَٰدِلُنَا فِى قَوْمِ لُوطٍ ۝٧٤ إِنَّ إِبْرَٰهِيمَ لَحَلِيمٌ أَوَّٰهٌ مُّنِيبٌ ۝٧٥ يَٰٓإِبْرَٰهِيمُ أَعْرِضْ عَنْ هَٰذَآ ۖ إِنَّهُۥ قَدْ جَآءَ أَمْرُ رَبِّكَ ۖ وَإِنَّهُمْ ءَاتِيهِمْ عَذَابٌ غَيْرُ مَرْدُودٍ ۝٧٦

74. To lokacin da tsoro ya rabu da Ibrahimu, kuma albishir ya zo masa, (sai ya zama) yana muhawara da Mu game da mutanen Luɗu.

75. Lalle Ibrahimu tabbas mai haƙuri ne mai yawan ambato Allah mai yawan komawa gare Shi.

76. Ya kai Ibrahimu, ka kau da kai daga wannan. Lalle umarnin Ubangijinka ya zo; lalle kuwa azaba wadda ba mai kawar da ita za ta zo musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da mu cewa, yayin da tsoro ya rabu da Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da ya fahimci cewa waɗannan baƙin ba mutane ne ba mala'iku ne, ya kuma ji daga bakinsu cewa an aiko su ne su je su hallaka mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka ƙi jin gargaɗinsa, sai kuma ya fara jayayya da su game da hallaka mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), yana nema musu alfarmar a ɗan saurara musu zuwa wani ɗan lokaci ko sa tuba su yi imani su bar fajircin da suke yi, domin kuwa shi Annabi Ibrahimu mutum ne mai haƙuri da juriya, kuma mai yawan komawa ga Allah da yawan ambatonsa. To amma sai mala'ikun nan suka amsa masa da cewa, ya kau da kansa daga wannan batu na nema musu jinkiri, domin kuwa umarnin Allah na saukar musu da azaba ya riga ya zo, don haka azaba ce mai girma take tafe a kansu babu kuma mai iya kawar da ita da addu'a ko da jayayya ko da wani abu daban.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawa kamar sauran mutane suke wajen abin da yake bijiro musu na farin ciki ko baƙin ciki ko damuwa.

2. Wanda ya bari aka cutar da baƙonsa alhalin yana da ikon ba shi kariya, to lalle wannan zai zama abin kunya a gare shi.

3. Mutum mai hankali shi ne wanda ba zai cutar da baƙo ba, sai dai ya karrama shi.

4. Mutum mai hankali shi ne wanda yake tsawatarwa game da aikata mummunan aiki.

5. Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) baƙo ne a garin Sadum ba shi da dangi waɗanda za su hana a cutar da shi saboda ƙabilanci.

Suratu Hud (77-80)

وَلَمَّا جَآءَتْ رُسُلُنَا لُوطًا سِىٓءَ بِهِمْ وَضَاقَ بِهِمْ ذَرْعًا وَقَالَ هَٰذَا يَوْمٌ عَصِيبٌ ۝٧٧ وَجَآءَهُۥ قَوْمُهُۥ يُهْرَعُونَ إِلَيْهِ وَمِن قَبْلُ كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ ۚ قَالَ يَٰقَوْمِ هَٰٓؤُلَآءِ بَنَاتِى هُنَّ أَطْهَرُ لَكُمْ ۖ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَلَا تُخْزُونِ فِى ضَيْفِىٓ ۖ أَلَيْسَ مِنكُمْ رَجُلٌ رَّشِيدٌ ۝٧٨ قَالُوا۟ لَقَدْ عَلِمْتَ مَا لَنَا فِى بَنَاتِكَ مِنْ حَقٍّ وَإِنَّكَ لَتَعْلَمُ مَا نُرِيدُ ۝٧٩ قَالَ لَوْ أَنَّ لِى بِكُمْ قُوَّةً أَوْ ءَاوِىٓ إِلَىٰ رُكْنٍ شَدِيدٍ ۝٨٠

77. Lokacin kuma da manzanninmu suka zo wa Luḍu, sai aka ɓata masa rai saboda su, kuma zuciyarsa ta yi ƙunci saboda su, ya kuma ce: “Wannan rana ce mawuyaciya!”

78. Mutanensa kuwa suka zo masa suna gaggawa, da ma ko can sun zamanto suna yin munanan ayyuka. Ya ce: “Ya ku mutanena, ga ‘ya’yana nan mata, su suka fi tsarkaka a gare ku (ba maza ba), to ku kiyayi Allah, kada ku kunyata ni game da baƙina. Yanzu a cikinku ba wani mutum mai hankali?”

79. Suka ce: “Haƙiƙa ka sani ba mu da wani haƙƙi (na sha’awa) ga ‘ya’yanka mata, lalle kuma tabbas ka san abin da muke nufi!”

80. Ya ce: “Ina ma ina da ƙarfi da zan hana ku, ko kuwa ina da wata ƙaƙƙarfar majingina (da zan dogara da ita)?”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba mu labarin abin da ya faru lokacin da baƙin mala’iku suka isa alƙaryar Annabi Luḍu a cikin kamannin mutane kuma samari kyawawa, sai ya shiga damuwa saboda ganin su, ransa ya ɓaci domin ya san mutanensa ba za su ƙyale su ba; ko ta halin ƙaƙa sai sun neme su da aikin alfasha, har ma ya ce: “Wannan rana ce mawuyaciya a gare ni”, domin yana zaton za su fi ƙarfinsa a kansu. Sai kuwa abin da yake gudu ya auku, domin mutanensa sun yo tururuwa cikin gaggawa suna rige-rige da junansu da nufin kowa ya samu rabonsa. Da ma kuma wannan mummunar al’adar ta neman maza don biyan sha’awarsu ta zame musu jiki. Sai Annabi Luḍu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga ƙoƙarin jawo hankalinsu, yana musu tayin auren ‘ya’yansa mata, su aure su mana domin su suka fi tsarkaka a gare su maimakon neman maza. Ya ƙara gargaɗinsu da su ji tsoron Allah su kiyaye dokokinsa kada su kunyata shi a gaban baƙinsa. Ya ce musu: “Yanzu wai a cikinku babu wani mutum mai hankali?” Watau wanda zai tsawatar musu. To amma ina; hankalinsu ya riga ya ɓace. Sai suka ce masa, ai ya riga ya san cewa su fa ba ruwansu da matan balle su auri ‘ya’yansa ko sauran matan garinsu. Ai shi ya san abin da suke nema, watau buƙatarsu ita ce saduwa da maza kawai.Daga nan sai Annabi Luḍu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga cikin matsananciyar damuwa, yana tunanin ina ma a ce yana da ƙarfin da zai yi amfani da shi wajen kare baƙinsa, ko kuma yana da dangi a garin waɗanda za su taimaka masa faɗa da waɗannan miyagun mutanen?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin munin laifin mutanen Annabi Luḍu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Kamar yadda mutanen Annabi Luḍu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka jirkita tsarin rayuwar auratayya ta halittar da Allah ya yi sai su ma Allah ya yi musu azaba ta hanyar kifar da garinsu, sama ta koma ƙasa, ƙasa kuma ta koma sama.

3. Daga wannan azabar ce da Allah ya bayyana ya yi wa mutanen Annabi Luḍu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da yawa daga cikin malamai suke cewa, duk wanda aka same shi da laifin neman namiji, to za a kashe shi, ko ya taɓa yin aure ko bai taɓa yi ba. Abu Hanifa yana ganin za a jefo shi ne daga ƙololuwar sama, sannan a bi shi da jifa da duwatsu har sai ya mutu.

Suratu Hud (81-83)

قَالُواْ يَٰلُوطُ إِنَّا رُسُلُ رَبِّكَ لَن يَصِلُوٓاْ إِلَيۡكَۖ فَأَسۡرِ بِأَهۡلِكَ بِقِطۡعٖ مِّنَ ٱلَّيۡلِ وَلَا يَلۡتَفِتۡ مِنكُمۡ أَحَدٌ إِلَّا ٱمۡرَأَتَكَۖ إِنَّهُۥ مُصِيبُهَا مَآ أَصَابَهُمۡۚ إِنَّ مَوۡعِدَهُمُ ٱلصُّبۡحُۚ أَلَيۡسَ ٱلصُّبۡحُ بِقَرِيبٖ ٨١ فَلَمَّا جَآءَ أَمۡرُنَا جَعَلۡنَا عَٰلِيَهَا سَافِلَهَا وَأَمۡطَرۡنَا عَلَيۡهَا حِجَارَةٗ مِّن سِجِّيلٖ مَّنضُودٖ ٨٢ مُّسَوَّمَةً عِندَ رَبِّكَۖ وَمَا هِيَ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ بِبَعِيدٖ ٨٣

81. (Baƙin) suka ce: “Ya Luɗu, lalle mu manzannin Ubangijinka ne; ba za su iya isowa gare ka ba; don haka sai ka tafi kai da iyalanka cikin wani yanki na dare, kada kuwa ɗaya daga cikinku ya waiwaya, sai matarka kawai. Lalle ita kam abin da ya same su zai same ta. Lalle lokacin da aka ɗebar musu asuba ne kawai; shin asuba ba kurkusa take ba?

82. To lokacin da umarninmu ya zo sai Muka mai da samanta ƙasa (wato alƙaryar), Muka kuma yi mata ruwan duwatsu irin na soyayyen yumɓu wasu bayan wasu.

83. Waɗanda aka yi wa alama daga Ubangijinka. Ba kuwa nesa (dutsen) yake da azzalumai ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ci gaba da bayyana cewa, lokacin da malaʾikun suka ga Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga damuwa sosai da irin yadda mutanensa suka taso haiƙan suna ƙoƙarin sai sun ci mutuncin baƙinsa, sai suka kwantar masa da hankali, suka bayyana masa cewa, su ai malaʾiku ne waɗanda Allah ya aiko su don su hallaka mutanensa, don haka babu abin da za su iya yi musu na cutarwa. Suka kuma umarce shi da ya kwashe iyalansa kakaf cikin dare ya bar wannan garin, amma ban da matarsa domin ita ma tana tare da mutanen gari wajen kafirce wa Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Suka umarce shi da kada wani daga cikin iyalinsa ya waiwaya lokacin da suke fita daga garin, in ban da matarsa, ita kam abin da duk zai samu waɗannan mutane ita ma zai same ta. Suka kuma bayyana masa lokacin da Allah ya nufi azabarsa za ta saukar musu, watau lokacin asuba kuma lokaci ne na kurkusa.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin azabar da ta auka wa mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da waʾadin da aka ɗeba musu ya zo, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sa malaʾikun nan suka ɓaɓɓako da wannan alƙayar sai da suka ɗaga ta sama, sannan suka mayar da samanta ya koma ƙasa, ƙasa kuma ya koma sama, watau aka kifar da ita, sai kuma ya bi su da ruwan duwarwatsu na wutar Jahannama, kowane dutse kuma yana ɗauke da alamar wanda zai faɗa wa, umarni ne kuma daga Allah. Duwatsun suka yi ta zuba ɗaya bayan ɗaya har sai da suka hallaka su gaba ɗaya. Don haka wannan azaba ba nesa take ba ga duk wanda zai kwaikwayi irin zaluncin waɗannan miyagun mutane, idan Allah ya nufi yi masa azaba irin wannan yana iya yi, domin ba wani abu ne da zai gagare shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga Tauhidi shi ne farkon daʾawar annabawan Allah.

2. Haramcin tauye mudun awo ko sikeli.

3. Riba kaɗan ta halal ta fi albarka a kan dukiyar haramun mai yawa.

4. Haɗarin da ke tattare da zaluntar haƙƙin mutane.

5. Akwai haɗari babba a rayuwar waɗanda Allah zai hore musu niʾimominsa masu yawa, amma su riƙa bijire wa umarninsa.

6. Yana daga cikin zalunci a tauye wa mutum haƙƙinsa a komai na muʾamalar zamantakewa.

7. Imani shi ne yake saka wa mutum wadatar zuci, sai ‘yar ribar halal kaɗan da ya samu ta wadace shi ba sai ya cuci wani ba.

8. Wanda zuciyarsa ta riga ta lalace yawan dukiyarsa ba ya hana shi aikata cuta komai ƙanƙantarta.

Suratu Hud (84-86)

*وَإِلَىٰ مَدۡيَنَ أَخَاهُمۡ شُعَيۡبٗاۚ قَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥۖ وَلَا تَنقُصُواْ ٱلۡمِكۡيَالَ وَٱلۡمِيزَانَۖ إِنِّيٓ أَرَىٰكُم بِخَيۡرٖ وَإِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٖ مُّحِيطٖ ٨٤ وَيَٰقَوۡمِ أَوۡفُواْ ٱلۡمِكۡيَالَ وَٱلۡمِيزَانَ بِٱلۡقِسۡطِۖ وَلَا تَبۡخَسُواْ ٱلنَّاسَ أَشۡيَآءَهُمۡ وَلَا تَعۡثَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُفۡسِدِينَ ٨٥ بَقِيَّتُ ٱللَّهِ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَۚ وَمَآ أَنَا۠ عَلَيۡكُم بِحَفِيظٖ ٨٦

84. Kuma Mun aiko wa (mutanen) Madyana ɗanʾuwansu Shuʾaibu, ya ce: “Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta ba shi ba, kada kuma ku tauye mudu da sikeli; lalle ni ina ganin ku da alheri (wato wadata), kuma lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wata rana mai kewayewa.

85. “Kuma ya ku mutanena, ku cika mudu da sikeli da adalci; kada kuwa ku tauye wa mutane abubuwansu, kada kuma ku yaɗa ɓarna a bayan ƙasa.

86. “Abin da zai wanzu a gare ku na alheri a wurin Allah shi ya fi muku in kun kasance muminai. Ni kuma ba mai tsaron ku ba ne.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiga bayar da labarin Annabi Shuʾaibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya aika shi ga mutanen ƙasar *Madyana*, wadda ta taso tun daga garin *Maʾan*har ta dangane da Tabuka. *Madyanu*sunan wata ƙabila ce ta Larabawa da suka zauna a wannan wurin sai ake kiran sunan garin da sunansu. Annabi Shuʾaibu ya same su suna bautar gumaka ba Allah ba, sannan suna da taʾadar tauye mudun awo da sikeli na awon nauyi, don haka sai ya fara da kiran su zuwa bautar Allah shi kaɗai, sannan ya yi musu kashedi da tauye mudu da sikeli, ya ankarar da su irin niʾimar arzuki da Allah ya ba su; to kada su bijire masa, domin yana jiye musu tsoron azabar ranar lahira wadda za ta kewaye su ta koʾina.Annabi Shuʾaibu ya umarce su da su cika mudu da adalci yayin da suke yi wa mutane awo, hakanan su yi adalci lokacin da suke tsayar da sikeli; kada su cuci kowa, su ma kada a cuce su, kuma ya tsawatar musu a kan yin ɓarna a bayan ƙasa, ta hanyar fashi da makami, laifin da suka shahara da shi a lokacin. Ya nusar da su cewa, abin da za su samu na halal bayan sun ba wa mutane haƙƙoƙinsu cikakku shi ya fi musu alheri ya kuma fi albarka fiye da ƙwangen da suke yi wa mutane lokacin awo, ko tare mutane suna yi musu fashi da makami, don haka idan har su muminai ne da gaske, to su haƙura da ɗan abin da za su samu na halal. Ya kuma nuna musu cewa, shi ba wanda zai tsaya a kansu yana gadin su ba ne, yana lissafa ayyukansu don ya yi musu hisabi a kai; wannan aikin Allah ne masanin abin da yake ɓoye da na sarari.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Shuʾaibu mutum ne mai yawan salla har ya shahara da haka a cikin mutanensa.

2. An sharʾanta wa annabawan da suka gabata yin salla, sai dai kowa da irin yanayin tasa.

3. Duk wani annabi sananne ne a wurin mutanensa da kyawawan halaye tun gabanin annabcinsa.

4. Mai umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna lalle ya yi ƙoƙarin guje wa saɓa wa abin da yake waʾazi a kansa, domin daʾawarsa ta karɓu.

5. Dukiyar da Allah ya ba wa bawa, bai halatta ya yi abin da ya ga dama da ita ba sai dai yadda shariʾa ta ajiye.

6. Babban aikin annabawa shi ne kawo gyara gwargwadon ikonsu a cikin al'ummunsu.

7. Kada bawa ya dogara ga kowa sai ga Allah shi kaɗai, ya nemi taimakonsa da dacewa daga wurinsa a duk abin da yake yi.

8. Tsanar mai faɗar gaskiya bai dace ta hana karɓar gaskiyar da ta fito daga bakinsa ba.

9. Gargaɗi da tsoratarwa ta hanyar ba da labarin abin da ya sami wasu al'ummu a baya.

10. Kamar yadda Allah yake yafe wa mai laifi ya kankare masa zunubansa idan ya tuba, haka kuma yake son sa da nuna masa ƙauna.

Suratu Hud (87-90)

قَالُواْ يَٰشُعَيۡبُ أَصَلَوٰتُكَ تَأۡمُرُكَ أَن نَّتۡرُكَ مَا يَعۡبُدُ ءَابَآؤُنَآ أَوۡ أَن نَّفۡعَلَ فِيٓ أَمۡوَٰلِنَا مَا نَشَٰٓؤُاْۖ إِنَّكَ لَأَنتَ ٱلۡحَلِيمُ ٱلرَّشِيدُ ٨٧ قَالَ يَٰقَوۡمِ أَرَءَيۡتُمۡ إِن كُنتُ عَلَىٰ بَيِّنَةٖ مِّن رَّبِّي وَرَزَقَنِي مِنۡهُ رِزۡقٗا حَسَنٗاۚ وَمَآ أُرِيدُ أَنۡ أُخَالِفَكُمۡ إِلَىٰ مَآ أَنۡهَىٰكُمۡ عَنۡهُۚ إِنۡ أُرِيدُ إِلَّا ٱلۡإِصۡلَٰحَ مَا ٱسۡتَطَعۡتُۚ وَمَا تَوۡفِيقِيٓ إِلَّا بِٱللَّهِۚ عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُ وَإِلَيۡهِ أُنِيبُ ٨٨ وَيَٰقَوۡمِ لَا يَجۡرِمَنَّكُمۡ شِقَاقِيٓ أَن يُصِيبَكُم مِّثۡلُ مَآ أَصَابَ قَوۡمَ نُوحٍ أَوۡ قَوۡمَ هُودٍ أَوۡ قَوۡمَ صَٰلِحٖۚ وَمَا قَوۡمُ لُوطٖ مِّنكُم بِبَعِيدٖ ٨٩ وَٱسۡتَغۡفِرُواْ رَبَّكُمۡ ثُمَّ تُوبُوٓاْ إِلَيۡهِۚ إِنَّ رَبِّي رَحِيمٞ وَدُودٞ ٩٠

87. Suka ce: “Ya kai Shuʾaibu, yanzu sallarka ce take umartar ka da (ka sa) mu bar abin da iyayenmu suke bauta wa, kada kuma mu aikata abin da muka ga dama da dukiyoyinmu? Lalle tabbas kai ne mai haƙuri mai hankali!”

88. Ya ce: “Ya ku mutanena, me kuke gani ne, idan na kasance a kan bayyananniyar hujja daga Ubangijina, Ya kuma arzuta ni da kyakkyawan arziki daga gare Shi. Ba na kuma nufin in aikata abin da nake hana ku aikata shi. Ba komai nake nufi ba sai gyara iyakacin ikona. Kuma dacewata daga Allah kaɗai take. A gare Shi na dogara, kuma zuwa gare Shi ne zan koma.

89. “Kuma ya mutanena, kada saɓa mini ya jawo muku irin abin da ya sami mutanen Nuhu ko mutanen Hudu ko kuma mutanen Salihu, ku ma ya same ku. Mutanen Luɗu kuwa ba nesa suke da ku ba.

90. “Kuma ku nemi gafarar Ubangijinku, sannan ku tuba gare Shi. Lalle Ubangijina Mai yawan rahama ne Mai nuna ƙauna.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, Annabi Shuʾaibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mutanensa waʾazi da gargaɗi a kan abubuwa biyu, na farko, bautar wani ba Allah ba; na biyu, tauye mudu da sikeli. Su kuma sai suka mayar masa da martani a kan waɗannan abubuwa biyu da yake ƙoƙarin hana su aikatawa, suka ce masa sallarsa ce, watau ibadarsa ta sa shi yake ƙoƙarin raba su da addinin iyayensu na bautar gumaka? Watau dai ba za su daina shirka ba, saboda sun gaje ta ne

daga iyayensu. A kan abu na biyu kuma suka nuna masa cewa, dukiyarsu mallakinsu ne, don haka bai isa ya hana su aikata abin da suka ga dama da ita ba, na tauye mudu da sikeli. Cikin izgili da tsokana suka ƙara da ce masa: Lalle kai ne mai haƙuri mai hankali. Watau da har kake iya gane abin da ma ba mu gane ba. Ko kuma suna faɗa masa irin yadda a da suka ɗauke shi kafin ya fara yi musu waʾazi, sun ɗauke shi mutum ne mai haƙuri da juriyar zama da mutane, kuma mai hankali, to mene ne yanzu ya same shi da har ya sa shi irin waɗannan maganganu?

Daga nan sai Annabi Shuʾaibu ya mayar musu da martani da cewa, yaya za su yi idan har shi yana kan hujja bayyananniya daga Allah Ubangijinsa, kuma ya ba shi arzuki na halal, ya kuma ba shi annabta? Kuma ba yana nufin ya hana su wani mummunan aiki ba kamar tauye mudu da sikeli sannan shi kuma ya saɓa ma wannan ya aikata abin da yake hana su aikatawa ba. Ya tabbatar musu da cewa, buƙatarsa ɗaya ce a wurinsu, ita ce samar da gyara a cikinsu gwargwadon ikonsa, su kuma fahimci Tauhidi su kaɗaita Allah, su daina cutar junansu a muʾamalarsu da juna, kuma Allah ne kaɗai zai yi masa dace cikin wannan aiki da ya ɗora masa, kuma gare shi kaɗai ya dogara, kuma gare shi zai koma.

Annabi Shuʾaibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da yi wa mutanensa kashedi da su yi hattara kada tsananin gaba da shi ta sa su bijire wa abin da yake gargaɗinsu a kai, daga ƙarshe irin azabar da ta samu mutanen Nuhu da mutanen Hudu da mutanen Salihu su ma ta same su. Mutanen Annabi Luɗu ba nesa suke da su ba, watau garuruwansu ko zamaninsu. Domin Suna da labarin abin da ya same su na azaba yayin da suka saɓa wa annabawansu.

Sai kuma ya sake kiran su zuwa ga neman gafarar Ubangijinsu a kan laifuffukan da suke yi, su tuba su gyara ayyukansu, lalle Ubangiji mai rahama ne mai tsananin nuna ƙauna ga masu tuba da neman gafara

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin ƙiyayya ga mai faɗar gaskiya na iya hana fahimtar gaskiyar da yake faɗa.

2. Allah yakan ba da kariya ga mumini ta hanyoyin da shi ma bai san da su ba, yakan ba shi kariya ta hanyar danginsa ko da sun kasance kafirai ne.

3. Idan bijire wa Allah ta tsananta to sai a saurari saukar azabarsa.

Suratu Hud (91-93)
قَالُواْ يَٰشُعَيۡبُ مَا نَفۡقَهُ كَثِيرٗا مِّمَّا تَقُولُ وَإِنَّا لَنَرَىٰكَ فِينَا ضَعِيفٗاۖ وَلَوۡلَا رَهۡطُكَ لَرَجَمۡنَٰكَۖ وَمَآ أَنتَ عَلَيۡنَا بِعَزِيزٖ ٩١ قَالَ يَٰقَوۡمِ أَرَهۡطِيٓ أَعَزُّ عَلَيۡكُم مِّنَ ٱللَّهِ وَٱتَّخَذۡتُمُوهُ وَرَآءَكُمۡ ظِهۡرِيًّاۖ إِنَّ رَبِّي بِمَا تَعۡمَلُونَ مُحِيطٞ ٩٢ وَيَٰقَوۡمِ ٱعۡمَلُواْ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمۡ إِنِّي عَٰمِلٞۖ سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ مَن يَأۡتِيهِ عَذَابٞ يُخۡزِيهِ وَمَنۡ هُوَ كَٰذِبٞۖ وَٱرۡتَقِبُوٓاْ إِنِّي مَعَكُمۡ رَقِيبٞ ٩٣

91. Suka ce: “Ya kai Shuʾaibu, ba ma fahimtar da yawa daga abin da kake faɗa; lalle kuma tabbas muna ganin ka rarrauna a cikinmu, kuma ba don danginka ba da mun jefe ka; ba kuwa za ka gagare mu ba.”

92. Ya ce: “Ya ku mutanena, yanzu dangin nawa ne suka fi Allah girma a wurinku, kuka kuma ɗauke shi abin jefarwa a can bayanku? Lalle Ubangijina a kewaye Yake da (sanin) abin da kuke aikatawa.

93. ‘‘Kuma ya ku mutanena, ku yi aiki a kan irin hanyarku; ni ma lalle mai yin aiki ne (a kan tawa). Ba da daɗewa ba za ku san wanda azaba mai wulakantawa za ta zo masa, da kuma wanda yake maƙaryaci. Ku saurara, ni ma lalle mai sauraro ne tare da ku.’’

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana irin jayayyar da mutanen Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suke ta yi da shi, har ta kai ga yi masa barazanar kisa idan bai daina yi musu wa’azi ba, har da cewa, su fa ba sa ma fahimtar mafi yawan maganganunsa, kuma su suna yi masa kallon mai rauni ne a cikinsu, watau bai isa a ce shi ne zai riƙa faɗa musu irin maganganun da suke fitowa daga bakinsa ba, domin shi ba kowa ba ne a cikinsu; suna raga masa ne ma saboda alfarmar danginsa waɗanda su suna tare da su a addininsu ba su fita sun bi shi ba; in ba don haka ba da tuni sun jefe shi da duwatsu har mutuwa, domin ba zai gagare su ba.
Sai Shu’aibu ya mayar musu da martani cewa, yanzu dangina ne suka fi Allah girma a wurinsu, suka ƙyale shi don su ba don Allah ba, suka yi watsi da Allah da umarninsa, suka kuma ƙi yin imani da Annabinsa? Ya sake tabbatar musu da cewa, Allah yana sane da duk abin da suke aikatawa kuma zai yi musu sakayya a kansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Annabi Shu’aibu ya gane mutanensa sun yi nisa cikin kafirci; lalama da lallashi ba sa ƙara musu komai sai taurin kai, sai ya ɗauki matakin yi musu gargaɗin saukar azabar Allah a kansu da cewa, su ci gaba da bin hanyar da suka zaɓa wa kawunansu ta kafirci da zaluntar juna, shi ma zai ci gaba da bin tasa hanyar wadda Allah ya zaɓa masa, amma kuma su kwana da sanin cewa, ba da jimawa ba za su gane wanda azabar wulaƙanci za ta saukar masa, da wanda yake maƙaryaci tsakanin su da shi. Don haka shi da su duk su saurari hukuncin Allah a kansu.

Suratu Hud (94-95)
وَلَمَّا جَآءَ أَمۡرُنَا نَجَّيۡنَا شُعَيۡبٗا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ بِرَحۡمَةٖ مِّنَّا وَأَخَذَتِ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ ٱلصَّيۡحَةُ فَأَصۡبَحُواْ فِي دِيَٰرِهِمۡ جَٰثِمِينَ ٩٤ كَأَن لَّمۡ يَغۡنَوۡاْ فِيهَآۗ أَلَا بُعۡدٗا لِّمَدۡيَنَ كَمَا بَعِدَتۡ ثَمُودُ ٩٥

94. Lokacin kuwa da umarninmu ya zo Muka tserar da Shu’aibu tare da waɗanda suka yi imani da shi da wata rahama daga gare mu; tsawa kuma ta kama waɗanda suka kafirta, sai suka wayi gari cikin gidajensu a duddurƙushe, (ba rai).

95. Kamar daɗai ba su taɓa zama ba a cikinsu (gidajen) ba. Ku saurara; halaka ta tabbata ga (mutanen) Madyana kamar yadda Samudawa suka halaka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana aukuwar azabar da Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake tsoratar da mutanensa da ita, kuma lokacin da azabar ta zo Allah cikin rahamarsa ya tserar da Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka yi imani tare da shi, su kuma mutanensa azzalumai wata tsawa mai tsanani ta kama su nan da nan suka halaka baki ɗaya, suka wayi gari a yashe matattu a cikin gidajensu kamar daɗai ba su taɓa rayuwa a cikinsu ba. Tabbas mutanen Madyana sun yi nesa daga samun rahamar Allah, kamar yadda Samudawa mutanen Annabi Salihu su ma suka yi nesa daga gare ta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi game da bin shugabanni a kan saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Fir’auna ne zai jagoranci mutanensa zuwa wutar Jahannama a ranar alƙiyama.

3. Fir'auna tabbas ya mutu kafiri.

Suratu Hud (96-99)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا وَسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٍ ٩٦ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَإِيْهِۦ فَٱتَّبَعُوٓاْ أَمۡرَ فِرۡعَوۡنَۖ وَمَآ أَمۡرُ فِرۡعَوۡنَ بِرَشِيدٖ ٩٧ يَقۡدُمُ قَوۡمَهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فَأَوۡرَدَهُمُ ٱلنَّارَۖ وَبِئۡسَ ٱلۡوِرۡدُ ٱلۡمَوۡرُودُ ٩٨ وَأُتۡبِعُواْ فِي هَٰذِهِۦ لَعۡنَةٗ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ بِئۡسَ ٱلرِّفۡدُ ٱلۡمَرۡفُودُ ٩٩

96. Haƙiƙa kuma Mun aiko Musa da ayoyinmu da hijjoji bayyanannu.

97. Zuwa ga Fir'auna da manyan fadawansa, sai suka bi umarnin Fir'auna; amma kuma umarnin Fir'auna ba a kan hanya yake ba.

98. Zai jagoranci mutanensa ranar alƙiyama sai ya shigar da su wuta. Kuma tir da shiga wannan mashiga.

99. Aka kuma bi su da la'ana a wannan (duniyar) da kuma ranar alƙiyama. Irin wannan kyauta kuwa da aka yi musu ta munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, ya aika Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga Fir'auna da manyan fadawansa da hujjoji bayyanannu masu tabbatar da gaskiyar abin da ya zo da shi na kaɗaita Allah da bauta. To amma sai waɗannan fadawa suka biye wa Fir'auna, suka yarda da kafircinsa alhalin al'amarin Fir'auna gaba ɗaya ba a kan daidai yake ba. Don haka sai ya hallakar da su gaba ɗaya duniya da lahira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ranar alƙiyama Fir'auna zai shugabanci mutanensa, yana gaba suna bin sa a baya har sai ya shigar da su wutar Jahannama. Tir da wannan mashiga da zai jefa su cikinta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya bi su da la'ana tun a nan duniya, sun rasa rahamarsa, to hakanan ma a lahira zai bi su da wannan la'anar, ba su babu samun tsira. Tabbas wannan kyauta ta la'ana har iri biyu ta yi matuƙar muni gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Labaran da Allah ya bayar a Alƙur'ani duk gaskiya ne.

2. Wuraren da al'ummun farko suka rayu a cikinsu, wasu kufansu yana nan, wasu kuma an shafe komai da ya dangance su.

3. Duk abin da wani zai riƙe da sunan bauta ba zai tsinana masa komai ba yayin da azabar Allah ta zo.

4. Haɗarin aikata zalunci. Mafi girman zalunci kuwa shi ne yin shirka da Allah.

5. Azzalumi ko ya samu wani iko ko mulki to na ɗan lokaci ne, dole ne sai ya gushe ba da jimawa ba, amma kuma tsinuwar waɗanda ya zalunta za ta yi ta bin sa har tashin alƙiyama.

Suratu Hud (100-102)

ذَٰلِكَ مِنۡ أَنۢبَآءِ ٱلۡقُرَىٰ نَقُصُّهُۥ عَلَيۡكَۖ مِنۡهَا قَآئِمٞ وَحَصِيدٞ ١٠٠ وَمَا ظَلَمۡنَٰهُمۡ وَلَٰكِن ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡۖ فَمَآ أَغۡنَتۡ عَنۡهُمۡ ءَالِهَتُهُمُ ٱلَّتِي يَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مِن شَيۡءٖ لَّمَّا جَآءَ أَمۡرُ رَبِّكَۖ وَمَا زَادُوهُمۡ غَيۡرَ تَتۡبِيبٖ ١٠١ وَكَذَٰلِكَ أَخۡذُ رَبِّكَ إِذَآ أَخَذَ ٱلۡقُرَىٰ وَهِيَ ظَٰلِمَةٌۚ إِنَّ أَخۡذَهُۥٓ أَلِيمٞ شَدِيدٌ ١٠٢

100. Waɗannan suna daga labarun alƙaryu da Muke labarta maka su; daga cikinsu akwai waɗanda suke tsaye da waɗanda suke a rushe.

101. Ba Mu kuwa zalunce su ba, sai dai su ne suka zalunci kansu; allolinsu da suke bauta wa ba Allah ba, ba su maganta musu komai ba, lokacin da umarnin Ubangijinka ya zo; ba su kuwa ƙara musu komai ba in ban da halaka.

102. Haka kuwa damƙar Ubangijinka take idan ya damƙi alƙaryu yayin da suka yi zalunci. Haƙiƙa damƙarsa mai raɗaɗî ce mai tsanani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da Annabi (ﷺ) cewa, labaran da yake ba shi a cikin wannan Alƙur'ani duka gaskiya ne. Daga cikin al'ummu da ya ba shi labarin halakar da su, akwai waɗanda har yanzu sauran kufansu yana nan bai ɓace ba, akwai kuma waɗanda an share su kwata-kwata daga bayan ƙasa, babu sauran wata alamarsu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, abin da ya auka musu na halaka ya same su ne saboda laifukansu na kafirce wa annabawansa, don haka ba zaluntar su ya yi ba, su ne dai suka zalunci kawunansu, saboda sun riƙi wasu alloli suna bauta musu ba Allah Maɗaukakin Sarki ba, to sai ga shi allolin nasu na ƙarya ba su maganta musu komai ba lokacin da azabar Allah ta abko musu, ba su ƙara musu komai ba sai halaka da hasara. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu mummunan kamu, to haka da man kamun Allah yake, duk sa'adda ya damƙi mutanen wani gari azzalumai a kowane lokaci ne to damƙarsa mai raɗaɗî ce mai tsanani.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah yana saurara wa azzalumi har sai lokacin da ya damƙe shi, to ba zai kuɓuce masa ba." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya karanta faɗar Allah: "Haka kuma damƙar Ubangijinka take, idan ya damƙi alƙaryu yayin da suka yi zalunci, haƙiƙa damƙarsa mai raɗaɗî ce mai tsanani." [Bukhari #4686 da Muslim #2583].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mai jin tsoron azabar lahira ne kaɗai yake ɗaukar izina da wa'azi daga ayoyin Allah.

2. Annabawa da mala'iku da salihai ba za su yi ceto ba a ranar alƙiyama sai da izinin Allah.

3. Aljanna da ni'imominta da wutar Jahannama da azabar cikinta madawwama ne har abada ba za su gushe ba.

4. Mumini wanda yake fasiƙi Allah yana fitar da shi daga wutar Jahannama ya saka shi Aljanna saboda imaninsa.

5. Babu wani wanda maganarsa take zama hujja a shari'a in ban da Allah da annabawansa.

6. Dole ne kowa sai ya sami rabonsa da Allah ya rubuta masa a duniya na arzuki da lafiya da makamantan wannan. Samun kaso mai tsoka na jin daɗin duniya da arzikin cikinta ba ya nuna fifiko ko nagarta a wurin Allah, domin Allah yana bayar da duniya ga wanda yake ƙauna da wanda ma ba ya ƙauna, amma ba ya bayar da imani da nagartaccen addini sai ga wanda yake ƙauna.

Suratu Hud (103-109)

إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَةً لِّمَنْ خَافَ عَذَابَ ٱلْآخِرَةِۚ ذَٰلِكَ يَوْمٌ مَّجْمُوعٌ لَّهُ ٱلنَّاسُ وَذَٰلِكَ يَوْمٌ مَّشْهُودٌ ﴿١٠٣﴾ وَمَا نُؤَخِّرُهُۥٓ إِلَّا لِأَجَلٍ مَّعْدُودٍ ﴿١٠٤﴾ يَوْمَ يَأْتِ لَا تَكَلَّمُ نَفْسٌ
إِلَّا بِإِذْنِهِۦۚ فَمِنْهُمْ شَقِيٌّ وَسَعِيدٌ ﴿١٠٥﴾ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ شَقُوا۟ فَفِى ٱلنَّارِ لَهُمْ فِيهَا زَفِيرٌ وَشَهِيقٌ ﴿١٠٦﴾ خَٰلِدِينَ فِيهَا مَا دَامَتِ ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلْأَرْضُ إِلَّا مَا شَآءَ رَبُّكَۚ إِنَّ
رَبَّكَ فَعَّالٌ لِّمَا يُرِيدُ ﴿١٠٧﴾ *وَأَمَّا ٱلَّذِينَ سُعِدُوا۟ فَفِى ٱلْجَنَّةِ خَٰلِدِينَ فِيهَا مَا دَامَتِ ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلْأَرْضُ إِلَّا مَا شَآءَ رَبُّكَ عَطَآءً غَيْرَ مَجْذُوذٍ ﴿١٠٨﴾ فَلَا تَكُ فِى
مِرْيَةٍ مِّمَّا يَعْبُدُ هَٰٓؤُلَآءِۚ مَا يَعْبُدُونَ إِلَّا كَمَا يَعْبُدُ ءَابَآؤُهُم مِّن قَبْلُۚ وَإِنَّا لَمُوَفُّوهُمْ نَصِيبَهُمْ غَيْرَ مَنقُوصٍ ﴿١٠٩﴾

103. Lalle game da wannan akwai aya ga wanda ya ji tsoron azabar lahira. Wannan kuwa rana ce da za a tattara mutane a cikinta, kuma wannan rana ce wadda kowa zai halarta.

104. Kuma ba ma jinkirta ta sai zuwa lokaci ƙayyadadde.

105. Ranar da za ta zo ba wani mai rai da zai yi magana sai da izininsa. To daga cikinsu akwai taɓaɓɓe da kuma mai rabauta.

106. To waɗanda suka taɓe suna cikin wuta suna ta kururuwa da ihu a cikinta.

107. Suna madawwama a cikinta matuƙar sammai da ƙasa suna nan a dawwame, sai dai abin da Ubangijinka Ya ga dama. Lalle Ubangijinka Mai yawan aikata abin da Yake nufi ne.

108. Amma waɗanda aka yi musu dace da rabauta, to suna cikin Aljanna suna masu dawwama a cikinta matuƙar sammai da ƙasa suna nan a dawwame, sai dai abin da Ubangijinka Ya ga dama, (wannan) kyauta ce marar yankewa.

109. To kada ka zamo cikin kokwanto dangane da abin da waɗannan suke bauta wa. Ba sa bauta sai kamar yadda iyayensu a da can suke bautar. Lalle kuma tabbas za Mu cika musu sakamakonsu ba da tauyewa ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, game da damƙar da ya yi wa alƙaryun da suka yi zalunci da halaka su da ya yi ba shakka akwai aya abin lura game da wannan, amma ga wanda ya ji tsoron azabar ranar lahira. Wannan rana kuwa ita ce ranar da Allah zai tattara mutane gaba ɗaya a cikinta domin yi musu hisabi, don haka dole sai kowa ya halarci wannan taro. Allah kuma ya bayyana cewa, yana jinkirta zuwan wannan rana ce har sai ƙayyadadden lokacin da aka aje mata ya zo. Lokacin da za ta zo kuwa to babu wani rai da zai iya yin wata magana ta kare kai ko ta ceton wani sai idan Allah ya yi masa izini. Mutane kuma za su kasu gida biyu ne a wannan ranar, watau taɓaɓɓu ‘yan wuta, da kuma marabauta ‘yan Aljanna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon kowannensu. Su dai taɓaɓɓu su ne za su shiga wutar Jahannama suna ta kururuwa da ihu a cikinta saboda tsananin azabarta. Za su kuma ci gaba da zama a cikinta har abada matuƙar sammai da ƙasa suna nan, sai wanda Allah ya ga damar fitar da shi daga cikin muminai masu laifuka. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa (ﷺ) cewa, lalle shi mai aikata abin da ya ga dama ne, babu mai tilasta shi ko ya hana shi.
Su kuma marabauta, waɗanda aka yi musu gyaɗar-dogo tun a nan duniya, suka ba da gaskiya suka yi ayyuka na ƙwarai, to su kam za a kai su gidan Aljanna, su kuma dawwama a cikinta matuƙar sammai da ƙasa suna nan, sai wanda Allah ya ga damar shigar da shi wuta kafin shigarsa Aljannar saboda zunubinsa, lalle ni’imar Allah ga ‘yan Aljanna marar yankewa ce.
Faɗar Allah: “Matuƙar sammai da ƙasa suna nan a dawwame.” wani salon magana ne irin wanda Larabawa suke yi idan suna nufin zartar da wani abu wanda zai ci gaba da wanzuwa har abada, to sai su faɗi haka. Amma da wuta da Aljanna ba za su gushe ba har abada.

An karɓo daga Abu Saʾid Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Za a zo da mutuwa cikin kamannin wani farin rago mai sofanen baƙi, sai mai shela ya yi shela ya ce: "Ya ku ʻyan Aljanna." Sai su leƙo su duba, sai ya ce: "Shin kun san wannan?" Sai su ce: "E, mutuwa ce." Dukkansu sun taɓa ganin ta. Sannan ya yi shela, ya ce: "Ya ku ʻyan wuta." Sai su leƙo su duba, sai ya ce: "Shin kun san wannan?" Sai su ce: "E, wannan mutuwa ce." Dukkansu sun taɓa ganin ta. Sai ya yanka shi, Sannan mai shela ya ce: "Ya ku ʻyan Aljanna, ku yi ta zama har abada babu mutuwa, ku ma ʻyan wuta ku yi ta zama har abada babu mutuwa." [Bukhari #4730 da Muslim #2849].

Bayan Allah ya gama bayanin sakamakon kafirai da muminai a lahira, sai kuma ya ci gaba da tsoratar da mushirikai da irin azabar halakarwar da ta faru ga al'ummun da suka gabace su, su yi hattara kada su ma ta faru gare su. Allah kuma ya ja hankalin Annabi (ﷺ) cewa, kada ya zamo mai kokwanton ɓacin abin da mushirikai suke bauta wa, ba su da wata hujja ta shariʾa ko ta hankali da ke nuna gaskiyar abin da suke kai, abin da kawai ya ja su ga bauta wa wasu ba Allah ba shi ne kwaikwayon iyayensu. Allah kuwa ya yi alƙawari a kan cewa, zai cika musu sakamakonsu na azaba ba tare da ya tauye wani abu daga ciki ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin zuciyar Manzon Allah (ﷺ) game da turjiya da yake fuskanta daga Ƙuraishawa da cewa, irin wannan ya faru ga annabawan da suka gabace shi.

2. Tsoratarwa da yin kashedi a kan sassaɓawa a shaʾanin aƙida.

3. Yahudawa sun sassaɓa a addininsu, sun kasu ƙungiyoyi masu yawa, masu mabambanta aƙidu.

Suratu Hud (110-111)
وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ فَٱخْتُلِفَ فِيهِ ۚ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ لَقُضِىَ بَيْنَهُمْ ۚ وَإِنَّهُمْ لَفِى شَكٍّ مِّنْهُ مُرِيبٍ ﴿١١٠﴾ وَإِنَّ كُلًّا لَّمَّا لَيُوَفِّيَنَّهُمْ رَبُّكَ أَعْمَٰلَهُمْ ۚ إِنَّهُۥ بِمَا يَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿١١١﴾

110. Haƙiƙa kuma Mun bai wa Musa Littafi, sai aka sassaɓa a game da shi. Ba don kuwa wata kalma da ta rigaya daga Ubangijinka ba, to lalle da an yi hukunci a tsakaninsu. Kuma lalle suna cikin matuƙar kokwanto game da shi (Alƙur'ani).

111. Kuma lalle kowannensu tabbas sai Ubangijinka Ya cika musu sakamakon ayyukansu. Lalle Shi Masanin abin da suke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, ya ba wa Annabi Musa littafin Attaura wanda zai sanya Banu Israʾila su haɗa kansu wajen bin umarninsa da barin haninsa, to amma maimakon haka sai suka shiga saɓani game da wannan, suka rungumi aƙidu mabambanta. To ba don maganar da Allah ya yi ta cewa zai saurara wa masu laifi ba zai gaggauto musu azaba ba, zai bar su sai ranar alƙiyama, to da tuni sun gamu da matsananciyar azaba tun a nan duniya. Allah ya tabbatar da cewa, kafirai na Larabawa da Yahudu da Nasara lalle suna cikin shakka mai sa kokwanto game da lamarin Alƙurʾani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lalle su waɗannan masu jayayya a kan Alƙurʾani suna ƙaryata shi, Allah ba zai ƙyale su hakanan ba, dole ne za su gamu da sakamakonsu cikakke, wanda ya aikata kyakkyawa ya ga kyakkyawa; wanda kuwa ya aikata mummuna shi ma ya ga mummuna. Lalle Allah masanin abin da suke aikatawa ne a sarari da ɓoye.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haɗarin karkata ga azzalumai da nuna musu ƙauna.

2. Tsayawa a kan abin da shari'a ta zo da shi da guje wa ƙari a addini, watau ƙago bidi'o'i a addini da sunan neman lada.

3. Annabawa su kansu ba sa yin gaban-kansu a addini suna tsayawa ne inda aka tsayar da su.

4. Wanda yake tare da Annabi shi ne wanda ya tsaya kan shiriyarsa bai karkace ba.

5. Wajibi ne ka hana azzalumi zaluncinsa idan kana da ikon yin haka, idan ba ka da shi to dole ne ka guji tarayya da shi wajen aikata zalunci, idan ba haka ba to azabar Allah za ta haɗa da kai.

6. Girman azabar azzalumai.

Suratu Hud (112-113)
فَٱسۡتَقِمۡ كَمَآ أُمِرۡتَ وَمَن تَابَ مَعَكَ وَلَا تَطۡغَوۡاْۚ إِنَّهُۥ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ١١٢ وَلَا تَرۡكَنُوٓاْ إِلَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ فَتَمَسَّكُمُ ٱلنَّارُ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِنۡ أَوۡلِيَآءَ ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ ١١٣

112. Don haka sai ka tsaya totar kamar yadda aka umarce ka kai da waɗanda suka tuba tare da kai, kada kuwa ku wuce iyaka. Lalle Shi (Allah) Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

113. Kuma kada ku karkata zuwa ga waɗanda suka yi zalunci, sai wuta ta shafe ku, ba ku kuwa da wasu majiɓinta lamura ba Allah ba, sannan ba za a taimake ku ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da muminai da tsayawa kyam a kan umarnin Allah a kan miƙaƙƙiyar hanya ta aikata abin da aka umarce su da barin abin da aka hana su da kuma gaskata duk abin da aka labarta musu, kada su karkata zuwa dama ko hagu, su dawwama a kan haka. Lalle Allah mai ganin abin da suke aikatawa ne, don haka zai yi musu sakamako a kansu.

An karɓo daga Sufyanu ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ce: "Ya Manzon Allah, faɗa mini wata magana a Musulunci wanda ban da kai ba zan sake tambayar wani ba game da ita" Sai ya ce: "Ka ce: "Na yi imani da Allah, sannan ka tsaya ƙyam." [Muslim #38].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗe su da su guji karkata ko ta halin ƙaƙa zuwa ga kafirai azzalumai da sunan kara ko soyayya, sai wuta ta shafe su a dalilin hakan, alhalin ba su da wasu masoya waɗanda za su kuɓutar da su daga wannan azabar, ko su taimaka musu in ba Allah ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni a kan kiyaye salloli a lokutansu tare da kula da sharuɗɗansu.

2. Kyakkyawan aiki yana share ƙananan laifuka idan an nisanci manya.

3. Yalwar rahamar Allah da tausayinsa ga bayinsa.

4. Girman sha'anin salla a cikin sauran ibadu.

5. Kiyaye sallolin asuba da la'asar da yin su a kan lokacinsu.

6. Haƙuri a kan biyayya ga Allah da Manzonsa da haƙuri a kan wata ƙaddara marar dadi, yana daga cikin ihsani, watau isa matuƙa wajen kyautata ibada.

7. Wajabcin samuwar wata ƙungiya ta jama'a masu umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna. Samuwarsu ce za ta hana uƙubar Allah ta sauka a kan al'ummar.

8. Kasancewar mutum shi a karan kansa mutumin kirki ne, amma bai damu da gyara kowa ba, wannan ba zai wadatar da shi ba; sai dai ya zamanto mai ƙoƙarin kawo gyara cikin al'umma.

Suratu Hud (114-117)

وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ طَرَفَيِ ٱلنَّهَارِ وَزُلَفًا مِّنَ ٱلَّيۡلِۚ إِنَّ ٱلۡحَسَنَٰتِ يُذۡهِبۡنَ ٱلسَّيِّـَٔاتِۚ ذَٰلِكَ ذِكۡرَىٰ لِلذَّٰكِرِينَ ١١٤ وَٱصۡبِرۡ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١١٥ فَلَوۡلَا كَانَ مِنَ ٱلۡقُرُونِ مِن قَبۡلِكُمۡ أُوْلُواْ بَقِيَّةٖ يَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡفَسَادِ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّنۡ أَنجَيۡنَا مِنۡهُمۡۗ وَٱتَّبَعَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مَآ أُتۡرِفُواْ فِيهِ وَكَانُواْ مُجۡرِمِينَ ١١٦ وَمَا كَانَ رَبُّكَ لِيُهۡلِكَ ٱلۡقُرَىٰ بِظُلۡمٖ وَأَهۡلُهَا مُصۡلِحُونَ ١١٧

114. Ka kuma tsai da salla farkon rana da ƙarshenta da kuma farkon dare. Lalle kyawawan (ayyuka) suna shafe munana. Wannan tunasarwa ne ga masu tunawa.

115. Kuma ka yi haƙuri, domin lalle Allah ba Ya tozarta ladan masu kyautatawa.

116. Ina ma da a ce an samu mutanen kirki daga tsarekun da suka gabace ku da za su riƙa hana yaɗuwar ɓarna a bayan ƙasa? Sai 'yan kaɗan kawai (aka samu) daga waɗanda Muka tserar cikinsu. Waɗanda kuma suka yi zalunci sai suka bi abin da aka wadata su da shi, suka kuwa zamanto masu laifi.

117. Kuma Ubangijinka bai kasance mai hallaka alƙarya ba da zalunci alhali kuwa mutanenta suna masu gyara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da tsayar da salla a farkon rana da ƙarshenta, watau sallar asuba da sallar magariba; wasu malaman suka ce sallar asuba da ta la'asar ne; wasu kuma suna ganin su ne sallar asuba a farkon rana, azahar da la'asar kuma a ƙarshen rana; sai kuma farkon dare, watau sallar isha'i, ko kuma magariba da isha'i. Wasu malamai suna ganin wataƙila wannan ayar an saukar da ita ne gabanin a farlanta salloli biyar, watau a wannan lokacin salloli biyu kaɗai ake yi, ɗaya kafin hudowar rana, ta biyu kuwa bayan faɗuwar rana, sai kuma ƙiyamullaili da aka farlanta wa Annabi (ﷺ) da al'ummarsa, daga baya aka shafe wajabcinta daga kan al'umma sai Manzo kaɗai. Wasu kuma suka ce shi ma an shafe masa wajabcin.
Sannan Allah ya bayyana cewa, ayyukan ƙwarai suna kankare laifin munanan ayyuka da suka gabace su.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya Manzon Allah, na samu wata mace a wani lambu, na yi komai da ita amma ban sadu da ita ba; na sumbace ta, na kuma rungume ta, amma ban da wannan ba abin da na yi da ita; don haka ka yi mini abin da ka ga dama." Sai Annabi (ﷺ) bai ce masa komai ba. Sai mutumin ya juya ya tafi. Sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Allah ya rufa masa asiri shi kuma ya ƙi rufa wa kansa asiri." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya bi shi da kallo sannan ya ce: "Ku dawo mini da shi." Sai suka dawo da shi wurin Manzon Allah

(ﷺ). Sai Annabi ya karanta masa wannan ayar ta 114. Sai Mu'azu ya ce: "Wannan nasa ne shi kaɗai ko na dukkan mutane ne?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "A'a, na dukkan mutane ne." [Muslim #2763].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Salloli biyar da sallar Juma'a zuwa wata sallar Juma'ar da azumin watan Ramadan zuwa wani azumin watan Ramadan, suna kankare laifukan da suke tsakaninsu matuƙar an nisanci manyan laifuka." [Bukhari #528 da Muslim #667].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da yin haƙuri, ya kuma labarta masa girman ladan masu haƙuri, domin Allah ba ya tozarta ladan masu kyautatawa; yana karɓar kyawawan ayyukansu ya yi musu sakayya da mafi kyan abin da suka aikata.
To bayan Allah ya ambaci hallakar al'ummun da suka gabata a dalilin sun ƙaryata manzanninsu, ya kuma bayyana cewa yawancinsu sun saki hanyar Allah; waɗanda aka ba wa littattafai daga cikinsu ma an samu sun gurɓata littattafan, wanda yin haka zai iya haifar da ɓacewar addinai gaba ɗaya daga doron ƙasa. To amma Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nusantar da cewa saboda samun wasu mutanen kirki daga cikinsu, waɗanda suke kiran mutane zuwa ga kyawawan ayyuka suke hana munana, wannan ya haifar da amfani mai yawa a cikin al'ummunsu. To da Allah ya tashi hallaka mutanensu kafirai sai su ya tserar da su. Allah ya tabbatar da cewa su waɗannan azzalumai sun yi ta morewarsu ne kawai sun ƙi su fahimci gaskiya su bi ta, don haka suka zamanto masu laifi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzo (ﷺ) cewa, Allah ba zai halaka wata alƙarya ba idan har mutanen cikinta masu gyara ne a bayan ƙasa; yakan hallaka garin da mutanensa suke maɓarnata ne, masu aikata laifuka da zalunci a bayan ƙasa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rabuwar mutane zuwa addinai daban-daban da ra'ayoyi daban-daban wata hikima ce daga Allah don ya jarrabi bayinsa, ya tantance mai son gaskiya da mai bin son zuciya.

2. Waɗannan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya so da rahamarsa ba sa saɓani a kan tushen addini, watau kaɗaita Allah da bauta da gaskata manzanni.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawari sai ya cika wutar Jahannama da mabiyan Iblis cikin mutane da aljannu.

4. Labaran mutanen da suka gabata a Alƙur'ani ba su kasance domin nishaɗantarwa ba; manufarsu tabbatar da zuciyar mumini a kan gaskiya da wa'azi da tunatarwa ga masu tsoron Allah.

5. Allah shi kaɗai ne masanin gaibun sammai da ƙasa.

6. Ibadar bawa ba za ta yiwu ba sai da taimakon Allah da tallafinsa, don haka ya haɗa tsakanin umarni da bauta masa da umarni a kan dogaro da shi wuri guda.

Suratu Hud (118-123)
وَلَوۡ شَآءَ رَبُّكَ لَجَعَلَ ٱلنَّاسَ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗۖ وَلَا يَزَالُونَ مُخۡتَلِفِينَ ١١٨ إِلَّا مَن رَّحِمَ رَبُّكَۚ وَلِذَٰلِكَ خَلَقَهُمۡۗ وَتَمَّتۡ كَلِمَةُ رَبِّكَ لَأَمۡلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنَ ٱلۡجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ أَجۡمَعِينَ ١١٩ وَكُلّٗا نَّقُصُّ عَلَيۡكَ مِنۡ أَنۢبَآءِ ٱلرُّسُلِ مَا نُثَبِّتُ بِهِۦ فُؤَادَكَۚ وَجَآءَكَ فِي هَٰذِهِ ٱلۡحَقُّ وَمَوۡعِظَةٞ وَذِكۡرَىٰ لِلۡمُؤۡمِنِينَ ١٢٠ وَقُل لِّلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ ٱعۡمَلُواْ

عَلَىٰ مَكَانَتِكُمۡ إِنَّا عَٰمِلُونَ ١٣٥ وَٱنتَظِرُوٓاْ إِنَّا مُنتَظِرُونَ ١٣٦ وَلِلَّهِ غَيۡبُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَإِلَيۡهِ يُرۡجَعُ ٱلۡأَمۡرُ كُلُّهُۥ فَٱعۡبُدۡهُ وَتَوَكَّلۡ عَلَيۡهِۚ وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ١٣٧

118. Kuma da Ubangijinka Ya ga dama da lalle Ya yi mutane al'umma ɗaya (a kan addini ɗaya). Ba kuwa za su gushe suna masu saɓawa juna ba.

119. Sai wanda Ubangijinka Ya yi wa rahama. A kan haka kuwa Ya halicce su; kuma Kalmar Ubangijinka ta tabbata (cewa): Lalle zan cika Jahannama da aljannu da mutane baki ɗaya.

120. Muna labarta maka kowanne daga labarun manzanni, abin da za Mu kwantar da zuciyarka da shi. Gaskiya kuwa ta zo maka cikin wannan (Surar) da izina da gargaɗi ga muminai.

121. Kuma ka ce da waɗanda ba sa yin imani: "Ku yi aiki a irin hanyarku, mu ma za mu yi aiki (a irin tamu).

122. "Kuma ku saurara, haƙiƙa (mu ma) masu sauraro ne."

123. Kuma (sanin) gaibu na sammai da na ƙasa na Allah ne, kuma gare Shi ake komar da dukkanin al'amari. To ka bauta masa kuma ka dogara gare Shi. Ubangijinka kuwa ba gafalalle ba ne ga abin da kuke aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cikakkiyar Ƙudurarsa ta cewa da ya ga dama da ya halicci mutane gaba ɗaya a kan manufa ɗaya ko a kan addini ɗaya ko ya halicce su muminai, ko dukkansu kafirai; to amma bai yi hakan ba, shi ya sa mutane suka zamanto koyaushe cikin sassaɓawa a tsakaninsu, saboda bin son zuciya da jahilici, sai fa wanda Ubangiji ya yi masa rahama ya nuna masa gaskiya, ya kuma ba shi ikon bin ta; to waɗannan su ne ba sa saɓawa da junansu a kan sha'anin kaɗaita Allah da bauta da gaskata manzanninsa. Kuma da man Allah ya halicce su ne don wannan jarrabawar, don haka daga cikinsu aka samu mai rabauta ya riƙi gaskiya, aka samu taɓaɓɓe wanda zai riƙi ƙarya da ɓata.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kalmarsa ta riga ta tabbata a kan lalle sai ya cika wutar Jahannama da mabiya Shaiɗan cikin mutane da aljannu. Allah kuma shi ne mai cikakkiyar hikima.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Aljanna da wuta sun yi jayayya, sai Aljanna ta ce: "Me ya sa ni babu masu shiga cikina sai raunanan mutane da marasa matsayin cikinsu?" Ita kuma wuta sai ta ce: "An zaɓa mini masu girman kai da masu nuna isa." Sai Allah ya ce wa Aljanna: "Ke dai rahamata ce, ina yin rahama da ke ga wanda na ga dama." Ya ce wa wuta kuma: "Ke kuma azabata ce, ina azabta wanda na ga dama da ke. Kowaccenku kuma zan cika ta." To amma ita Aljanna sai ya zamana akwai sauran wuri a cikinta, har sai da Allah ya ƙagi wasu halittu ya zaunar da su cikin sauran wurin da bai cika ba a Aljanna. Wuta kuwa sai faɗa take yi cewa: "Shin ko akwai wani ƙari?" Har sai da Ubangiji Mabuwayi ya saka ƙafarsa a cikinta, sai ta ce: "Na rantse da Buwayarka ya isa, ya isa." [Bukahri #4850 da Muslim #2846].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci hikimar da ke tattare da ba wa Manzon Allah ƙissoshin annabawa da cewa, duk labaran da yake ba shi na manzannin da suka gabace shi tare da al'ummunsu, da abin da ya gudana a tsakaninsu na jayayya da musu, da juriyar da annabawan suka yi yayin da mutanensu suka ƙaryata su, suka kuma cutar da su, da yadda Allah ya taimaka wa manzanninsa tare da mabiyansu ya tserar da su ya kuma halaka maƙiyansu kafirai, duk Allah yana ambata masa waɗannan ne domin ya tabbatar masa da zuciyarsa a kan gaskiya, ya ƙarfafe ta a kan haƙuri da juriya, don ya zama mai koyi da 'yan'uwansa annabawa da suka gabace shi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar wa Manzonsa cewa, gaskiya ce ta zo masa a cikin wannan Surar wadda ta ƙunshi tarihin annabawa da al'ummunsu, da yadda ya tserar da annabawa da muminai, ya hallaka maƙiyansu, da kuma waʾazi da tunatarwa ga mumainai da ta ƙunsa, domin su ne masu amfana da tunatarwa.
Sai kuma ya umarci Manzonsa ya faɗa wa waɗanda ba su ba da gaskiya da abin da ya zo da shi daga Allah ba cewa, su yi aiki a irin hanyarsu ta kauce wa gaskiya da bijire mata, shi ma tare da waɗanda suka yi imani da shi za su yi aiki a irin hanyarsu ta dagewa a kan gaskiya da kira zuwa ga Allah da haƙuri a kan haka. Ya ƙara da cewa, su saurari abin da zai same su, shi ma tare da sahabbansa za su yi sauraro. Haƙiƙa Allah ya cika wa Manzonsa alƙawarinsa, ya taimake shi ya ba shi nasara a kan maƙiyansa, ya ɗaukaka addininsa a kan kafirci.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana a ƙarshen Surar da cewa shi kaɗai ne masanin gaibu na sammai da ƙasa, kuma gare shi ne ake komar da dukkan alʾamari ranar alƙiyama, don haka ya umarci Annabinsa da ya bauta masa shi kaɗai, ya dogara gare shi shi kaɗai cikin dukkan lamuransa, shi Allah ba gafalalle ne game da abin da bayinsa suke aikatawa ba, yana sane da komai, kuma zai saka wa kowa a kan ayyukansa kyawawa ko munana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da muʾujizar Alƙurʾani.

2. Muhimmancin koyon harshen Larabci da darajarsa, saboda shi ne harshen da aka saukar da mafificin littafi da shi, watau Alƙurʾani.

3. Babu masu fahimtar Alƙurʾani sai masu hankali.

4. Labaran da Alƙurʾani ya zo da su sun fi kowane irin labarai kyau da inganci, saboda gaskiyar da ke cikinsu da salo da azanci mai ƙayatarwa.

5. Kafin saukar da Alƙurʾani, Annabi (ﷺ) bai san komai na shariʾa da ƙissoshin annabawa ba.

6. Tabbatar da gaskiyar annabcin Annabi (ﷺ).



12.Suratu Yusuf

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna "*Suratu Yusuf* " saboda ta ƙunshi labarin Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) gaba ɗaya. Babu wata sura da ta zo da labarinsa daki-daki in ban da wannan Surar. Ba a kuma ambaci sunansa a ko'ina ba sai a nan da kuma cikin "*Suratul An'am*" da "*Suratu Ghafir*".

An Karɓo daga Uƙbatu ɗan Amiru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Na ce wa Manzon Allah (ﷺ) ya karanta mini *Suratu Hud* da *Yusuf*….". [Ahmad#17418, Nasa'i#953].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Na kasance a garin Himsu (cikin ƙasar Syria), sai wasu suka roke ni in karanta musu Alƙur'ani, sai na karanta musu *Suratu Yusuf* ". [Bukhari#5001 da Muslim#801].

Ya zo a hadisin Amru ɗan Maimunu da yake ba da labarin kashe Sayyiduna Umar, yana cewa: "Umar ya kasance idan ya wuce ta tsakanin sahu biyu (na masallata) sai ya ce: "Ku daidaita sahu", sai ya tabbata babu wani bigire tsakanin sahu da sahu sannan sai ya wuce gaba ya yi kabbarar harama. Wani lokaci sai ya karanta *Suratu Yusuf* ko kuma ya karanta *Suratun Nahl*, ko makamancin haka a raka'ar farko" watau a sallar Asuba. [Bukhari#3700].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa, Sura ce *Makiyya*.

3. Jerin Saukarta:
An saukar da ita bayan *Suratu Hud*. Ta kuma sauka ne a dunƙule a lokaci guda.

4. Adadin Ayoyinta:
Tana da ayoyi ɗari da goma sha ɗaya (111).

5. Babban Jigonta:
• Bayani a kan cewa kyakkyawan ƙarshe yana tabbata ne ga masu tsoron Allah da haƙuri, komai runtsi da wahalhalun rayuwa.
•Lallashin Annabi (ﷺ) da sahabbansa da kwantar musu da hankali.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
Ita ce surar da ta zo da ambaton ƙissar Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a dunƙule a wuri guda. Babu wata ƙissa da ta zo kamar haka a cikin Alƙur'ani sai wannan ƙissar ita kaɗai.
Daga fittattun abubuwan da ta ƙunsa kuwa sun haɗa da:
• Faɗar wata falala ta Alƙur'ani wajen ba da labari cikin salo mai cike da hikima da jan hankali.

• Bayanin mafarkin Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da makircin da ‘yan’uwansa suka ƙulla masa da hassadar da suka nuna masa.
• Yadda ayarin matafiya suka tsinci Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a kururramar rijiya sannan suka sayar da shi a Masar; da makircin da ya gamu da shi daga matar Azizu da wasu daga cikin matan Masar.
• Shigarsa kurkuku duk da cewa ya tabbata ba shi da wani laifi da yadda ya zama mai kira zuwa ga Allah a cikin kurkukun.
• Mafarkin Sarkin Masar da fassarar da Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mafarkinsa da wanke shi daga zargin matar Azizu da fitowarsa daga kurkuku da karɓar aikin mai kula da taskokin arzikin ƙasa da yadda Allah ya ɗaukaka sha’aninsa.
• Haɗuwar Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ‘yan’uwansa ba tare da sun gane shi ne Yusuf ba, da yadda ya nemi idan sun tashi dawowa Masar su zo tare da ɗan’uwansa da kuma bayanin yadda Allah ya shirya masa dabarar riƙe ɗan’uwansa, sai kuma bayanin abin da ya biyo bayan haka na faɗawar mahaifinsu cikin baƙin ciki da tashin hankali.
• Haɗuwar Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ‘yan’uwansa da yadda ya bayyana musu kansa, ya kuma tuna musu abin da suka aikata a gare shi tare da yi musu afuwa, sannnan kuma da yadda ya umarce su su koma wajen babansu su jefa masa rigar Annabi Yusufu a fuskarsa domin ganinsa ya dawo masa.
• Zuwansu Masar gaba ɗaya tare da mahaifinsu da karramawar da Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mahaifansa da ‘yan’uwansa.
• Ɗauraya da ta biyo bayan ƙissar Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a inda Allah ya bayyana abin da yake nuna cewa Alƙur’ani daga wajensa yake da abin da yake ƙara tabbatar da gaskiyar Annabi Muhammadu (ﷺ), ya kuma yi bayanin aikin Annabi (ﷺ) da matakin da mushirikai suka ɗauka game da da’awarsa, tare da tabbatar da cewa, Annabi (ﷺ) ba shi ne farau a cikin manzanni ba, sannan kyakkyawan ƙarshe nasa ne shi da mabiyansa muminai.

Suratu Yusuf (1-3)

الٓرۚ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ١ إِنَّآ أَنزَلۡنَٰهُ قُرۡءَٰنًا عَرَبِيّٗا لَّعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ٢ نَحۡنُ نَقُصُّ عَلَيۡكَ أَحۡسَنَ ٱلۡقَصَصِ بِمَآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ وَإِن كُنتَ مِن قَبۡلِهِۦ لَمِنَ ٱلۡغَٰفِلِينَ ٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. *ALIF LAM RA*. Waɗannan ayoyi ne na Littafi mabayyani.

2. Lalle Mu Muka saukar da shi Alƙur’ani da (harshen) Larabci don ku hankalta.

3. Mu ne Muke labarta maka (labari) mafi kyan labartawa ta hanyar yi maka wahayin wannan Alƙur’ani, ko da yake gabaninsa kana cikin marasa sanin(sa).

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da wasu haruffa kamar yadda ya yi a wasu surori da suka gabata. Babbar hikimar da aka ambata game da waɗannan haruffa ita ce, Allah yana nuni ne da su zuwa ga mu’ujizar Alƙur’ani wanda duk masu fasahar Larabawa suka kasa kawo irinsa duk kuwa da cewa suna magana da irin haruffan da Alƙur’ani ya sauka da su. Wannan yana ƙara tabbatar da cewa Alƙur’ani maganar Allah ce ba ta wani ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa, waɗannan ayoyi da aka saukar cikin wannan Sura suna cikin bayyanannun ayoyin da wannan littafi na Alƙur'ani ya ƙunsa.
Sai kuma ya bayyana wa Manzonsa cewa, shi ne ya saukar da Alƙur'ani cikin harshen Larabci domin Larabawa da sauran masu jin wannan harshe su fahimci ma'anonin da ya ƙunsa.Sai kuma ya faɗa masa cewa, shi ne zai ba shi mafi kyan labarai domin ingancinsu da kyakkyawan zubin salonsu da tsarinsu da sauƙin fahimtarsu, ta hanyar saukar masa da Alƙur'ani wanda littafi ne da babu kamarsa. Sai kuma ya tabbatar wa Manzon Allah (ﷺ) cewa, kafin ya saukar masa da wannan littafin yana cikin waɗanda ba su san komai ba game da shari'o'i da kuma ƙissoshin da ya ƙunsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin tausayi da kuma amincewar da ke tsakanin ɗa da mahaifinsa. Abu ne mai kyau uba ya sakar wa 'ya'yansa fuska ta yadda za su iya kawo masa matsalolinsu domin samun mafita.

2. Ladabin Annabi Yusuf ga mahaifansa da tausasa harshe yayin magana da su.

3. Bayar da labarin mafarki ga mutum mai ilimi da hankali domin samun kyakkyawar shawara.

4. Idan Allah ya nufi bawansa da wani babban al'amari a rayuwarsa yakan iya nuna masa wasu alamomin tun daga farko, kamar yadda ya nuna wa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) alamomin samun ɗaukaka a rayuwarsa, kuma hakan ya tabbata.

5. Mafarkin annabawa gaskiya ne saboda sun fi kowa gaskiya.

6. Ganin 'yan'uwan Annabi Yusufu a kamannin taurari yana nuni da cewa za su yi kyakkyawan ƙarshe.

7. Yara suna iya yin mafarki kuma ya zamanto na gaskiya.

8. Cusa sanin girman Allah da dasa tarbiyya a zuciyar yaro, ya gane cewa komai ya samu to zaɓi ne na Allah ko da bayan girmansa ne.

9. Shaiɗan koyaushe yana shiga tsakanin 'yan'uwa domin jefa gaba da ƙiyayya a tsakaninsu.

10. Yana da kyau mutum ya riƙa taka-tsantsan cikin lamarinsa don gudun aukawa cikin aikin da-na-sani.

Suratu Yusuf (4-6)

إِذْ قَالَ يُوسُفُ لِأَبِيهِ يَـٰٓأَبَتِ إِنِّى رَأَيْتُ أَحَدَ عَشَرَ كَوْكَبًا وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ رَأَيْتُهُمْ لِى سَٰجِدِينَ ۝٤ قَالَ يَـٰبُنَىَّ لَا تَقْصُصْ رُءْيَاكَ عَلَىٰٓ إِخْوَتِكَ فَيَكِيدُوا۟ لَكَ كَيْدًا ۖ إِنَّ ٱلشَّيْطَـٰنَ لِلْإِنسَـٰنِ عَدُوٌّ مُّبِينٌ ۝٥ وَكَذَٰلِكَ يَجْتَبِيكَ رَبُّكَ وَيُعَلِّمُكَ مِن تَأْوِيلِ ٱلْأَحَادِيثِ وَيُتِمُّ نِعْمَتَهُۥ عَلَيْكَ وَعَلَىٰٓ ءَالِ يَعْقُوبَ كَمَآ أَتَمَّهَا عَلَىٰٓ أَبَوَيْكَ مِن قَبْلُ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْحَـٰقَ ۚ إِنَّ رَبَّكَ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ۝٦

4. (Ka tuna) lokacin da Yusufu ya ce da babansa: "Ya babana, lalle na yi mafarkin taurari goma sha ɗaya da rana da wata, na gan su suna yi min sujjada."

5. Ya ce: "Ya ɗana, kada ka labarta mafarkinka ga 'yan'uwanka, sai su shirya maka makirci; lalle Shaiɗan maƙiyi ne mai bayyana ƙiyayya ga mutum.

6. "Kamar haka ne kuma Ubangijinka zai zaɓe ka Ya kuma sanar da kai wani abu daga fassarar mafarkai, Ya kuma cika ni'imarsa a gare ka da kuma ga iyalin Ya'aƙubu kamar yadda tun tuni Ya cika ta ga iyayenka Ibrahimu da Is'haƙa. Lalle Ubangijinka Masani ne Mai hikima."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiga ba wa Annabi (ﷺ) labarin Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da 'yan'uwansa. Ya fara da mafarkin da Annabi Yusufu ya yi, ya kuma faɗa wa mahaifinsa Annabi Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Annabi Yusufu shi ne ɗan Annabi Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ɗan Annabi Is'haƙa ɗan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Mai karamci ɗan mai karamci ɗan mai karamci, watau Yusufu ɗan Ya'aƙubu ɗan Is'haƙa ɗan Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi)." [Bukhari #3390].

An karɓo daga Abu Hurairata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa: "Wane ne cikin mutane ya fi karamci?" Sai ya ce: "Mafi karamcinsu a wurin Allah shi ne mafi tsoron Allah a cikinsu." Sai suka ce: "Ba a kan wannan muke tambaya ba." Sai ya ce: "Mafi karamcin mutane shi ne Yusufu, Annabin Allah ɗan Annabin Allah ɗan Annabin Allah ɗan Badaɗayin Allah…." [Bukhari #4689 da Muslim #2378].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiga ba wa Annabi (ﷺ) labarin mafarkin da Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi na taurari goma sha ɗaya da rana da wata, ya gan su sun faɗi a gabansa suna yi masa sujjada ta gaisuwa da jinjina. Da mahaifinsa ya ji wannan mafarki da ya yi sai ya gargaɗe shi tare da jan kunnensa da cewa, kada ya kuskura ya faɗa wa 'yan'uwansa wannan mafarki domin za su fahimci abin da ya ƙunsa na fifiko da ɗaukaka da Allah zai ba shi a kansu a nan gaba, har su zo gabansa su zube suna yi masa gaisuwar ban girma. Idan kuwa suka fahimci haka to hassada za ta shiga zukatansu game da shi, sai su shiga yi masa mugun shiri da makirci wanda zai cutar da shi. Domin Shaiɗan zai yi ta zuga su saboda mummunar gabar da ke tsakaninsa da mutane.
Malamai sun ambaci cewa, fassarar mafarkin Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ita ce: Taurari goma sha ɗaya yana nufin 'yan'uwansa su goma sha ɗaya; rana kuwa na nufin mahaifiyarsa; wata kuma yana nufin mahaifinsa Annabi Ya'aƙubu. Kuma mafarkin yana nuna canjin da zai faru nan gaba a rayuwar Annabi Yusufu da zai kai shi ga samun wani babban matsayi da za su zo gabansa su faɗi su yi sujjadar girmamawa da jinjina a gare shi.
Annabi Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da faɗa wa ɗansa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, a nan gaba Allah zai zaɓe shi ya ba shi ilimin fassarar mafarki, ya kuma cika masa ni'imominsa na duniya kamar annabta da mulki da na lahira, watau kyakkyawan sakamako na gidan Aljanna, kamar yadda ya cika wa iyayensa a can baya, watau Annabi Ibrahimu da Annabi Is'haƙa. Ba shakka kuma Ubangijinsa masani ne ga komai na ɓoye da na sarari da abin da yake cikin zukatan bayinsa, mai hikima ne, yana saka komai a muhallinsa yana ba wa kowa matsayinsa.

An karɓo daga Abu Ƙatada (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kyakkyawan mafarki daga Allah ne, idan ɗayanku ya yi mafarkin abin da yake so, to kada ya faɗa wa kowa sai masoyinsa; idan kuwa ya ga abin da yake ƙi a mafarki, to ya nemi tsarin Allah daga sharrin wannan mafarkin daga kuma sharrin Shaiɗan, ya yi tofi sau uku, kada kuma ya faɗa wa kowa labarin wannan mafarkin, to ba zai cutar da shi ba." [Bukhari #7044 da Muslim #2261].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ƙissar Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) tana cike da darussa masu ɗimbin yawa.

2. Bayanin haɗarin hassada wadda takan kai mai yin ta zuwa ga aikata mugun laifi kamar kisan kai.

3. Kishi wani abu ne da Allah ya halicce shi ga duk wani ɗan'adam, amma idan mutum ya sakar wa zuciyarsa ragama a kan kishi to Shaiɗan zai yi amfani da wannan damar ya ja shi zuwa ga hassada har ya kai shi ga kisan kai.

4. Sau da yawa mai laifi yakan fara ne da nema wa laifinsa wasu dalilai daga nan sai ya samu ƙarfin gwiwar zartar da mummunan ƙudurinsa na laifi.

5. Shaiɗan yakan yaudari mutum ta hanyar buɗe masa ƙofar tuba kafin ya aikata wani laifi, idan ya gamsar da shi a kan haka sai ya ingiza shi cikin aikata wannan laifin.

6. Idan ba za ka iya hana aikata ɓarna gaba ɗayanta ba, to ka yi ƙoƙari wajen rage mata girma da tasiri.

7. Hukuncin 'ya'yan Annabi Yaƙubu game da shi na fifita Yusufu da ɗan'uwansa a kansu ba daidai ba ne, mummunan zato da jahilci ne ya ja su ga shirya mummunan aiki.

8. Yawa da ƙarfi sukan rudî wasu har su kai ga aikata abin da bai dace ba.

Suratu Yusuf (7-10)
*لَّقَدۡ كَانَ فِي يُوسُفَ وَإِخۡوَتِهِۦٓ ءَايَٰتٞ لِّلسَّآئِلِينَ ٧ إِذۡ قَالُواْ لَيُوسُفُ وَأَخُوهُ أَحَبُّ إِلَىٰٓ أَبِينَا مِنَّا وَنَحۡنُ عُصۡبَةٌ إِنَّ أَبَانَا لَفِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ٨
ٱقۡتُلُواْ يُوسُفَ أَوِ ٱطۡرَحُوهُ أَرۡضٗا يَخۡلُ لَكُمۡ وَجۡهُ أَبِيكُمۡ وَتَكُونُواْ مِنۢ بَعۡدِهِۦ قَوۡمٗا صَٰلِحِينَ ٩ قَالَ قَآئِلٞ مِّنۡهُمۡ لَا تَقۡتُلُواْ يُوسُفَ وَأَلۡقُوهُ فِي غَيَٰبَتِ ٱلۡجُبِّ يَلۡتَقِطۡهُ بَعۡضُ ٱلسَّيَّارَةِ إِن كُنتُمۡ فَٰعِلِينَ ١٠

7. Haƙiƙa akwai ayoyi ga matambaya dangane da (labarin) Yusufu shi da 'yan'uwansa.

8. (Ka tuna) lokacin da ('yan'uwan) suka ce: "Lalle Yusufu da ɗan'uwansa babanmu ya fi son su da mu, ga mu kuwa jama'a masu yawa. Lalle babanmu yana cikin kuskure mabayyani.

9. "Ku kashe Yusufu ko kuma ku jefa shi wata ƙasa, (yin haka) zai juyo muku fuskar babanku, sai kuma ku kasance salihai bayansa."

10. Wani mai magana daga cikinsu ya ce: "Kada ku kashe Yusufu, ku jefa shi cikin duhun kururrumar rijiya, wasu ayarin matafiya za su tsince shi, in har haka za ku yi."

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, a game da labarin Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da 'yan'uwansa ba shakka akwai ayoyi da darussa masu ɗimbin yawa ga duk wani mai tambaya wanda zai so ya san abin da zai amfane shi ba wanda yake bijire wa gaskiya ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin lokacin da 'yan'uwan Yusufu suka haɗu don tattaunawa da shawarwari game da lamarin alaƙar mahaifinsu Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Yusufu shi da ɗan'uwansa shaƙiƙi Binyaminu, har suke rantsuwar cewa mahaifinsu ya fi son Yusufu da ɗan'uwansa Binyaminu a kansu tare kuwa da cewa su ne jama'a, watau su suka fi yawa don haka za su fi amfani a

wurinsa, amma duk da haka ya fifita son yara ƙanana a kansu, don haka suke ganin lalle mahaifinsu yana tabka babban kuskure cikin wannan lamari.
Sai suka fara tunanin hanyar da za su bi wajen kawar da Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga idon mahaifinsu don hankalinsa ya dawo kansu; sai wasu suka ce kamata ya yi kawai su kashe shi gaba ɗaya ko su jefar da shi can wata uwa duniya, mahaifinsu ya daina ganin sa gaba ɗaya; idan sun yi haka zai sa hankalin mahaifinsu ya dawo kansu. Su kuma in ya so daga baya sai su tuba su nemi yafiyar Allah.
To amma wani daga cikinsu ya tausaya wa Annabi Yusufu, ya nuna maganar kisa ta yi tsauri, don haka maimakon kisa su kai shi su jefa shi cikin wata kururrumar rijiya, idan sun yi haka buƙatarsu ta raba shi da mahaifinsa ta samu ba tare da sun yi kisan kai ba. Ta yiwu wasu ayarin fatake su tsince shi su yi awon gaba da shi zuwa ƙasarsu mai nisa su mayar da shi bawansu, ya gama rayuwarsa a can cikinsu, su kuma su mallake zuciyar mahaifinsu su kaɗai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba a zargin mutum idan ya nuna tsananin son ɗansa.

2. Tsananin ƙaunar Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ga ɗansa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana a fili.

3. Sun fara da yi wa mahaifinsu shaguɓe da nuna masa cewa, idan ya hana su fita da Yusufu to ya ɗauke su marasa amana kenan, don haka ya ga ya zama dole ya ƙyale shi ya bi su duk kuwa da ba ya so.

4. Ba a sauraron maganar mahassadi balle ma a yarda da alƙawarinsa, ko da kuwa ya fito ne a rigar mai nasiha.

5. Wani lokaci wasu sukan fake da kyakkyawar niyya ko son aikata alheri domin su cutar da wani.

6. Idan kana shakkar mutum, to kada ka buɗe masa ƙofar da zai cutar da kai. Yayin da Annabi Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna kyarkeci zai iya cinye Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai 'yan'uwansa suka samu hujjar da za su fake da ita idan sun salwantar da shi.

7. Wajibi ne 'yan'uwa su kare ɗan'uwansu daga duk abin da zai cutar da shi.

8. Garin da Annabi Yusuf da 'yan'uwansa suka taso an san shi da yawan kyarkeci masu kai wa mutane farmaki suna halaka su.

9. Annabi Ya'aƙubu ya nuna cewa, tafiyarsu da Yusufu kiwo za ta ɓata masa rai ne domin ya sa su daina nace masa da roƙo, domin duk ɗa na ƙwarai ba zai so ganin ɓacin ran mahaifinsa ba.

10. Tsoro wata ɗabi'a ce ta ɗan'adam, musamman tsoron abin da zai cutar, kamar namun daji masu farauta. Annabawa ma sukan ji tsoro irin wannan.

Suratu Yusuf (11-14)
قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا مَالَكَ لَا تَأۡمَنَّا عَلَىٰ يُوسُفَ وَإِنَّا لَهُۥ لَنَٰصِحُونَ ١١ أَرۡسِلۡهُ مَعَنَا غَدٗا يَرۡتَعۡ وَيَلۡعَبۡ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ١٢ قَالَ إِنِّي لَيَحۡزُنُنِيٓ أَن
تَذۡهَبُواْ بِهِۦ وَأَخَافُ أَن يَأۡكُلَهُ ٱلذِّئۡبُ وَأَنتُمۡ عَنۡهُ غَٰفِلُونَ ١٣ قَالُواْ لَئِنۡ أَكَلَهُ ٱلذِّئۡبُ وَنَحۡنُ عُصۡبَةٌ إِنَّآ إِذٗا لَّخَٰسِرُونَ ١٤

11. Suka ce: “Ya babanmu, me ya sa ne ba ka amince mana game da Yusufu, alhali kuwa lalle mu ba shakka masu kula da shi ne?

12. “Ka tura shi gobe tare da mu ya yi kiwo, ya kuma yi wasa, lalle kuma mu tabbas za Mu kiyaye shi.”

13. Ya ce: “Lalle tabbas tafiyarku da shi za ta baƙanta mini rai, ina kuma tsoron kyarkeci ya cinye shi ba da saninku ba.”

14. Suka ce: “Lalle idan kyarkeci ya cinye shi ga mu kuwa muna da yawa kuma majiya ƙarfi to ashe lalle mun taɓe.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da cewa, bayan ‘yan’uwan Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun amince da shawarar a jefa shi kururrumar rijiya, sai suka nufi babansu suka roƙe shi ya ba su dama su fita kiwo tare da Yusufu domin sun fahimci ba ya barin sa ya fita ko’ina tare da su. Suka nuna masa mamakinsu da har ba ya amince musu a kan Yusufu duk kuwa da cewa su masu nuna masa ƙauna ne, suna so masa duk abin da suke so wa kansu na alheri. Don haka suka roƙe shi da ya bar su gobe su fita da shi wurin kiwo shi ma ya shaƙata ya wala kamar yadda mahaifinsa yake ƙaunar ganin sa koyaushe. Suka tabbatar masa cewa lalle za su kula da shi ba za su bari wani abu ya cuce shi ba.
Da mahaifinsu Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ji wannan zance nasu, sai ya nuna musu cewa, saboda abubuwa biyu ne ba ya son bari su fita kiwo tare da Yusufu: Na ɗaya, zai damu idan ba ya ganin sa kusa da shi; na biyu, yana jin tsoron kada su shagala su manta da kula da shi har kyarkeci ya zo ya cinye shi suna can suna kiwonsu da harbe-harbensu. Suna jin wannan uzuri na biyu sai kawai suka riƙe shi a matsayin abin da za su kafa hujja da shi bayan sun gama aika-aikarsu. Sai ko suka tabbatar masa cewa, babu yadda za a yi su yi sakaci har kyarkeci ya cinye shi alhali ga su da yawa da ƙarfi, suka ce idan kuwa har haka ta faru to lalle sun tabka babbar hasara.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan Allah ya nufi bawansa da ɗaukaka yakan iya fara masa da jarrabawa.

2. Mai laifi ya fi son duhu a kan haske, domin ta duban fuskarsa akan iya gane shi, don haka ne suka je wa mahaifinsu da daddare ba da rana ba.

3. Kuka da hawaye shi kaɗai ba ya nuna gaskiyar mai da’awa, dole ne sai ya nuna dalilansa na zahiri masu gamsarwa.

4. Maganganun marar gaskiya cike suke da tufka da warwara. Sun yi wa mahaifinsu alƙawarin tafiya da ɗan’uwansu wurin kiwo, amma yanzu sun ce masa sun bar shi yana tsaron kayayyakinsu; sun faɗa masa za su kula da shi, amma sun nuna sun ƙyale shi shi kaɗai yana tsare musu kaya. Wannan duk tubka ce da warwara da ke nuna maganarsu ƙarya ce.

5. Marar gaskiya yakan fara tsarguwa shi kaɗai tun kafin a zarge shi, don haka suka ce: “Ba kuwa za ka gaskata mu ba ko da kuwa muna da gaskiya.”

6. Mai laifi yakan shirya wa mutane ƙarya don ta yi musu tasiri, to amma shi a karan-kansa ya tabbata ƙarya yake yi, ba kuma zai yarda da kansa ba ko da kuwa mutane sun yarda da shi.

7. Haƙuri mai kyau shi ne wanda babu raki a cikinsa.

8. Bawa ba zai iya haƙuri ba sai tare da taimakon Allah.

9. Wanda duk aka ɗora masa alhakin kula da wani al'amari, to dole ne ya tsaya ya kula da shi yadda ya dace.

10. Annabi Yaƙubu ya mayar da al'amarinsa ga Allah shi kaɗai sannan bai yi wani yunƙuri na gudanar da bincike a kan wannan lamarin ba, duk kuwa da rashin gamsuwarsa a kai, wa la'alla saboda ya tsufa sosai a lokacin, sannan ga shi babu mai taimaka masa sai waɗannan 'ya'yan nasa, su kuma su ne ake zargi a nan.

Suratu Yusuf (15-18)

فَلَمَّا ذَهَبُواْ بِهِۦ وَأَجۡمَعُوٓاْ أَن يَجۡعَلُوهُ فِي غَيَٰبَتِ ٱلۡجُبِّۚ وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡهِ لَتُنَبِّئَنَّهُم بِأَمۡرِهِمۡ هَٰذَا وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ١٥ وَجَآءُوٓ أَبَاهُمۡ عِشَآءٗ يَبۡكُونَ ١٦
قَالُواْ يَٰٓأَبَانَآ إِنَّا ذَهَبۡنَا نَسۡتَبِقُ وَتَرَكۡنَا يُوسُفَ عِندَ مَتَٰعِنَا فَأَكَلَهُ ٱلذِّئۡبُۖ وَمَآ أَنتَ بِمُؤۡمِنٖ لَّنَا وَلَوۡ كُنَّا صَٰدِقِينَ ١٧ وَجَآءُو عَلَىٰ قَمِيصِهِۦ
بِدَمٖ كَذِبٖۚ قَالَ بَلۡ سَوَّلَتۡ لَكُمۡ أَنفُسُكُمۡ أَمۡرٗاۖ فَصَبۡرٞ جَمِيلٞۖ وَٱللَّهُ ٱلۡمُسۡتَعَانُ عَلَىٰ مَا تَصِفُونَ ١٨

15. To lokacin da suka tafi da shi suka kuma haɗu a kan su saka shi cikin duhun kururrumar rijiya. Muka kuma yi masa wahayi (da cewa): "Wallahi (wata rana) za ka ba su labarin wannan al'amari nasu alhali su ba sa jin (haka zai faru)."

16. Suka kuwa dawo wa babansu da lisha suna kuka.

17. Suka ce: "Ya babanmu, mun tafi muna wasan rige muka kuma bar Yusufu wurin kayanmu, sai kyarkeci ya cinye shi. Ba kuwa za ka gaskanta mu ba ko da muna da gaskiya."

18. Suka kuma zo da jinin ƙarya a rigarsa. (Babansu) ya ce: "Ba haka ba ne, zuciyarku dai ta shirya muku wani abu. Saboda haka (ba ni da wani abin yi) sai haƙuri nagari; Allah kuma Shi ne wanda ake neman taimakonsa a kan abin da kuke sifantawa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, Annabi Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya amince ya bar `ya`yansa sun tafi kiwo tare da Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Bayan sun tafi da shi ne sai suka haɗu a kan zartar da shawararsu ta jefa shi cikin duhun kururrumar rijiya. Haka kuwa suka aikata. To bayan sun jefa shi ne Allah ya yi masa wahayi mai ƙunshe da albishir na kuɓutar da rayuwarsa da sake haɗa fuskarsa da ta 'yan'uwansa, har kuma ya ba da labarin abin da suka ƙulla masa na mugunta da makirci a lokacin da su ba za su iya gane shi ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana abin da 'yan'uwan Yusufu suka yi bayan dawowarsu gida wurin mahaifinsu, suka yi ƙoƙarin ɓoye masa gaskiyar aika-aikar da suka yi wa Yusufu. Da farko sai suka ƙi komawa gida sai a makare bayan isha'i gari ya yi duhu, sannan suka fara kukan alhinin abin da ya sami Yusuf, wai don Annabi Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yarda da su. Daga nan suka faɗa masa uzurin ƙarya na rashin dawowa da Yusufu, watau suka ce masa ai sun bar shi ne ya tsare musu kayayyakinsu su kuma suka tafi suna wasan tsere, ba su ankara ba sai zuwa suka yi suka tarar kyarkeci ya cinye Yusufu. To amma fa a faɗarsu mai yiwuwa ne ya ƙi yarda da su ko da kuwa gaskiya suka faɗa masa, watau domin tsananin son da yake nuna wa Yusufu kuma ga shi tun farko ya nuna musu yana jin tsoron kyarkeci ya cinye shi ba tare da sun kula ba. To suna ganin Annabi Yaƙubu ba zai yarda ya gaskata wannan arashin ba. Domin su tabbatar masa da gaskiyar maganarsu sai suka zo da rigar Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) caɓa-caɓa da jini, wai wannan alama ce da ke nuna gaskiyar maganarsu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai nutsu da maganarsu ba, domin alamar da suka kawo masa ce ta nuna rashin gaskiyarsu. In ba haka ba, ta yaya dabbar jeji za ta cinye mutum amma ba ta yayyaga rigarsa ba? Don haka sai ya ce musu, zukatansu ne kawai suka shirya musu wani abu, shi kam babu abin da zai iya sai kyakkyawan haƙuri bisa ga wannan jarraba da Allah ya ɗora masa, kuma Allah ne mai taimakon sa a kan wannan bayani nasu marar gamsarwa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan kawo wa bawansa ɗauki ta inda ba ya zato.

2. Wanda Allah yake tare da shi, to yakan ɗago shi daga ƙarƙashin ƙasa zuwa ƙololuwar samaniya domin ya nuna cikakken ikonsa a kansa.

3. Wata musiba a wurin wasu riba ce a wurin wasu: Yayin da mahaifin Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake cikin ƙuna da raɗaɗîn rashin ganin ɗansa, a daidai lokacin ne kuma wani yake cewa: "Abin farin ciki ya same ni, wannan yaro ne."

4. Faɗar Allah: "Kuma Allah masanin abin da suke aikatawa ne," ishara ce ga Annabi Muhammadu (ﷺ) cewa, Allah yana sane da cutarwar da Ƙuraishawa suke yi masa, kuma shi mai ikon hana su ne, amma ya ƙyale su domin ya ba wa Annabinsa (ﷺ) nasara daga ƙarshe, ya ɗora shi a kansu kamar yadda ya yi wa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

5. Sanin ilimin fassarar mafarki wata girmamawa ce daga Allah.

6. Abu mai martaba yakan iya fuskantar abin da zai sauko da martabarsa da ƙimarsa: Annabi Yusufu mai martaba ne kuma ɗan mai martaba, to amma an siffanta shi da siffofi uku na faɗuwar martaba, watau, an sayar da shi da ɗan kudî kaɗan; kudîn ma `yan dirhamai ne ƙididdigaggu; sannan, an bayyana cewa masu sayar da shi suna guje masa. Wannan ya nuna Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gamu da wani yanayi da ya sauko da martabarsa da ƙimarsa a wurin waɗanda suka tsince shi.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kyakkyawan tanadi, domin a lokacin da ya rasa tausayi da kulawa ta 'yan'uwantaka daga 'yan'uwansa, sai ya musanya masa da soyayya da kulawa irin ta uba ga ɗansa daga wani babban mutum na ƙasar Misra.

8. Abin izina a cikin ƙissoshin Alƙur'ani shi ne abubuwan da suka faru da darussan da ke cikinsu ba sunayen mutane da na wurare ba.

9. Duk wanda ya ja da Allah, to zai sha ƙasa, babu kuma mai iya kawar da abin da Allah ya nufi faruwarsa.

Suratu Yusuf (19-21)

وَجَآءَتۡ سَيَّارَةٞ فَأَرۡسَلُواْ وَارِدَهُمۡ فَأَدۡلَىٰ دَلۡوَهُۥۖ قَالَ يَٰبُشۡرَىٰ هَٰذَا غُلَٰمٞۚ وَأَسَرُّوهُ بِضَٰعَةٗۚ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِمَا يَعۡمَلُونَ ١٩ وَشَرَوۡهُ بِثَمَنِۭ بَخۡسٖ دَرَٰهِمَ مَعۡدُودَةٖ وَكَانُواْ فِيهِ مِنَ ٱلزَّٰهِدِينَ ٢٠ وَقَالَ ٱلَّذِي ٱشۡتَرَىٰهُ مِن مِّصۡرَ لِٱمۡرَأَتِهِۦٓ أَكۡرِمِي مَثۡوَىٰهُ عَسَىٰٓ أَن يَنفَعَنَآ أَوۡ نَتَّخِذَهُۥ وَلَدٗاۚ وَكَذَٰلِكَ مَكَّنَّا لِيُوسُفَ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلِنُعَلِّمَهُۥ مِن تَأۡوِيلِ ٱلۡأَحَادِيثِۚ وَٱللَّهُ غَالِبٌ عَلَىٰٓ أَمۡرِهِۦ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٢١

19. Da wasu ayarin matafiya suka zo sai suka tura mai nemo musu ruwa, sai ya zura gugansa (a rijiyar); sai ya ce: “Abin farin ciki ya same ni, wannan yaro ne;” suka kuma ɓoye shi a matsayin kayan kiri. Allah kuwa Masanin abin da suke aikatawa ne.

20. Suka kuma sayar da shi araha da ‘yan dirhamai ƙirgaggu, suka zamanto kuma suna masu tsantsami game da shi.

21. Wanda ya saye shi kuma daga Masar ya ce da matarsa: “Ki kyautata mazauninsa, muna fatan ya amfane mu, ko kuwa mu riƙe shi a matsayin ɗa.” (Allah Ya ci gaba da cewa): Kamar haka Muka tabbatar da Yusufu a bayan ƙasa don kuma Mu sanar da shi fassarar mafarkai. Allah kuwa Mai rinjaye ne a bisa alꞌamarinsa, sai dai yawancin mutane ba sa ganewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana abin da ya faru da Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan ‘yanꞌuwansa sun jefa shi cikin rijiya sun tafi sun bar shi. Yana ciki ne sai wasu ayarin matafiya zuwa Masar suka iso wurin, sai suka tura mai ɗebo musu ruwan sha, yana isa wurin rijiya sai ya jefa gugansa domin ya janyo ruwa, sai Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya riƙe igiyar gugar mutumin nan ya janyo shi yana tsammanin nauyin ruwa ne. Daga ganin kyakkyawan yaro ya fito daga rijiya sai ya shiga murna yana farin cikin ya yi tsintuwar yaro kyakkyawa.
Akwai yiwuwar shekarun Yusufu a lokacin ba su fi shekara goma zuwa sha huɗu ba, amma dai bai balaga ba.
Sai mutumin ya nufi ‘yanꞌuwansa da shi, su kuma suka ɗauke shi suka ɓoye shi a matsayin kadarar fatauci, Allah kuwa yana sane da duk abin da ke faruwa ga Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya bar shi ya ci gaba da faruwa ne saboda wata hikima tasa da ya riga ya ƙaddara.
Allah ya ci gaba da bayyana mana cewa, waɗannan ayarin fatake sun isa Masar tare da Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuma sun kai shi kasuwar bayi sun sayar da shi a kan ‘yan kuɗî kaɗan, watau dirhamai ƙididdigaggu, domin suna ƙyamar ci gaba da riƙe shi a wurinsu, ƙoƙarinsu dai su rabu da shi saboda sun kula ba ya da kamanni irin na bayi, kuma suna jin tsoron ‘yanꞌuwansa su gan shi su karɓe shi daga hannunsu. Wannan duk yana cikin rahamar Allah a gare shi, sai bai nufa ya daɗe sosai a hannunsu ba.
Allah ya bayyana cewa, wani babban mutum ne a Masar ya sayi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tafi da shi gidansa ya umarci matarsa da ta kyautata masaukinsa, ta hanyar kula da cinsa da shansa da suturarsa, domin wannan mutum ya ga alamar nan gaba Yusufu zai yi musu amfani sosai saboda cikar hankalinsa da ya gani, ko ma su mayar da shi ɗansu domin ba su sami haihuwa ba.
Allah ya bayyana cewa, kamar yadda ya kuɓutar da Annabi Yusufu daga kisa, ya fitar da shi daga tsohuwar rijiya, ya kuma kimsa ƙaunarsa a cikin zuciyar wannan babban mutum na Masar, to kamar haka ne ya kafa Yusufu a ƙasar Masar domin ya koyar da shi ilimin fassarar mafarki. Allah kuwa mai rinjaye ne bisa alꞌamarinsa, duk abin da ya ga dama shi zai wakana, babu mai tilasta shi (Mai tsarki da ɗaukaka), sai dai yawancin mutane kafirai ba su san haka ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya gina rayuwarsa a kan kyautatawa to Ubangiji zai saka masa da kyakkyawan sakamako duniya da lahira, ya tsare shi daga duk wani sharri da makirci.

2. Girman haɗarin da ke tattare da haɗuwar maza da mata a gidaje da sunan ‘yan aiki ko hadimai da keɓanta da matan da ba muharramai ba, kuma ba tare da aure ba.

3. Kariyar Allah ga bawansa daga faɗawa cikin saɓon Allah ita ce babban abin da yake katange bawa daga saɓon Allah.

4. Neman tsarin Allah shi ne katanga tsakanin bawa da duk wani abin ƙi.

5. Mutanen kirki ba sa manta alheri idan an yi musu.

6. Cin amanar mutum mai kyautatawa a kan dukiyarsa ko iyalinsa abu ne mai matuƙar muni.

7. Zina da matar aure zalunci ne ga mijinta.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tsare annabawa daga faɗawa cikin saɓon Allah.

9. Wajibi ne mumini ya kare kansa daga mai neman sa da aikata laifi, ya guje masa.

10. Ana matuƙar buƙatar hikima da dabaru a cikin aikin alƙalanci.

11. Halaccin amfani da alamomi wajen tantance mai gaskiya da marar gaskiya wajen hukunci.

12. Jarrabar da Annabi Yusufu ya gamu da ita wajen matar Azizu ta fi jarrabar jefa shi cikin duhun kururrumar rijiya girma, don haka haƙurin da ya yi ya jure ya fi girma a kan haƙurinsa na zaman rijiya saboda abubuwa kamar haka:
Haƙurinsa na rijiya dole ne, ba shi da wani zaɓi sai dai haƙurin, amma haƙurinsa a jarrabar gidan Azizu na zaɓi ne, domin da ya so yana iya amsa gayyatarta musamman abubuwan da za su ja hankalinsa a kai suna da yawa, daga cikinsu akwai:

• Halittar da Allah ya yi wa namiji ta sha'awar mace fiye da sha'awar ruwan sha ga mai jin ƙishirwa.
• Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a lokacin yana cikin ganiyar ƙuruciyarsa, sha'awar saurayi tana da ƙarfi matuƙa a tare da shi.
• Ga shi kuma tuzuru ba shi da matar aure ko kuyanga.
• Yana cikin halin baƙunta a wani gari. Mutum yakan iya barin wani abu saboda kunyar 'yan'uwa da dangi, amma ya iya aikata shi a garin da babu wanda ya san shi.
• Matar Azizu kyakkyawar mace ce matuƙa, ga ta da babban matsayi, kowane ɗaya daga cikin siffofin nan nata kan iya jan hankali da sauri.
• Kasancewar ita ta ba da kanta ga Yusufu.
• Ta jarrabu da neman aikata laifi ido-rufe.
• Annabi Yusufu yana ƙarƙashin ikonta sai yadda ta yi da shi.
• Ba ya jin tsoron ta sanar da wani domin ita ce ta fara neman sa ba shi ne ya neme ta ba.
• Kasancewarsa kamar bawa ko ɗa a gidan an saba ganin shigarsa da fitarsa, don haka babu wanda zai tuhume shi don ya gan shi ya fito daga inda take.

Duk waɗannan abubuwa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya danne zuciyarsa ya yi haƙuri bai saɓa wa Allah ba kuma bai ci amanar mai gidansa ba. Wannan babbar alama ce da ke nuna ya samu kariya ta Allah da muwafaƙarsa.

Suratu Yusuf (22-29)

وَلَمَّا بَلَغَ أَشُدَّهُۥٓ ءَاتَيۡنَٰهُ حُكۡمٗا وَعِلۡمٗاۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ٢٢ وَرَٰوَدَتۡهُ ٱلَّتِي هُوَ فِي بَيۡتِهَا عَن نَّفۡسِهِۦ وَغَلَّقَتِ ٱلۡأَبۡوَٰبَ وَقَالَتۡ هَيۡتَ لَكَۚ قَالَ مَعَاذَ ٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ رَبِّيٓ أَحۡسَنَ مَثۡوَايَۖ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ٢٣ وَلَقَدۡ هَمَّتۡ بِهِۦۖ وَهَمَّ بِهَا لَوۡلَآ أَن رَّءَا بُرۡهَٰنَ رَبِّهِۦۚ كَذَٰلِكَ لِنَصۡرِفَ عَنۡهُ ٱلسُّوٓءَ وَٱلۡفَحۡشَآءَۚ إِنَّهُۥ مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُخۡلَصِينَ٢٤ وَٱسۡتَبَقَا ٱلۡبَابَ وَقَدَّتۡ قَمِيصَهُۥ مِن دُبُرٖ وَأَلۡفَيَا سَيِّدَهَا لَدَا ٱلۡبَابِۚ قَالَتۡ مَا جَزَآءُ مَنۡ أَرَادَ بِأَهۡلِكَ سُوٓءًا إِلَّآ أَن يُسۡجَنَ أَوۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ٢٥ قَالَ هِيَ رَٰوَدَتۡنِي عَن نَّفۡسِيۚ وَشَهِدَ شَاهِدٞ مِّنۡ أَهۡلِهَآ إِن كَانَ قَمِيصُهُۥ قُدَّ مِن قُبُلٖ فَصَدَقَتۡ وَهُوَ مِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ٢٦ وَإِن كَانَ قَمِيصُهُۥ قُدَّ مِن دُبُرٖ فَكَذَبَتۡ وَهُوَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ٢٧ فَلَمَّا رَءَا قَمِيصَهُۥ قُدَّ مِن دُبُرٖ قَالَ إِنَّهُۥ مِن كَيۡدِكُنَّۖ إِنَّ كَيۡدَكُنَّ عَظِيمٞ٢٨ يُوسُفُ أَعۡرِضۡ عَنۡ هَٰذَاۚ وَٱسۡتَغۡفِرِي لِذَنۢبِكِۖ إِنَّكِ كُنتِ مِنَ ٱلۡخَٰطِـِٔينَ٢٩

22. Lokacin kuma da ƙarfinsa ya kawo sai Muka ba shi hikima da ilimi. Kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa.

23. Wadda kuma yake ɗakinta ta yi ƙoƙarin ya yi lalata da ita, ta kuwa kukkulle ƙofofi, ta kuma ce: ‘‘To ka zo mana!’’ Ya ce: ‘‘Allah Ya kiyashe ni! Lalle shi mai gidana ne, ya kyautata mazaunina. Lalle yadda al’amarin yake su azzalumai ba sa rabauta.’’

24. Lalle kuma ta yi niyyar ta rarumo shi, shi kuma ya yi niyyar karkata gare ta, ba don ya ga wata hujja ta Ubangijinsa ba. Kamar haka (Muka nuna masa hujjar) don Mu kawar da mummunan aiki da ɓarna daga gare shi. Lalle shi yana daga bayinmu zaɓaɓɓu.

25. Suka kuma yiwo rige wajen ƙofa, sai kuwa ta yaga rigarsa daga baya, kuma suka ci karo da mijinta daf da ƙofar, ta ce: ‘‘Ba wani sakamakon da ya cancanta ga wanda ya yi nufin mummunan abu da iyalinka in ban da kawai a ɗaure shi, ko kuwa a yi masa azaba mai raɗaɗi.’’

26. (Annabi Yusufu) ya ce: ‘‘Ita ce ta neme ni’’. Wani shaida kuwa daga danginta ya shaida (cewa): ‘‘Idan an yaga rigarsa ta gaba, to ta yi gaskiya shi kuwa yana cikin masu ƙarya.

27. ‘‘Idan kuwa an yaga rigarsa ta baya, to ta yi ƙarya shi kuwa yana daga masu gaskiya.’’

28. To yayin da (mijin nata) ya ga an yaga rigarsa ta baya ne, sai ya ce: ‘‘Lalle wannan yana daga irin makircinku; lalle makircinku kuwa yana da girma.’’

29. ‘‘Kai Yusufu, ka kau da kai daga wannan (magana). Ke kuma ki nemi gafarar laifinki, lalle ke kin zamanto daga masu laifi.’’

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata sabuwar jarraba da Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fuskanta wadda ta fi ta cikin rijiya hatsari. Watau yayin da Yusufu ya isa ganiyar ƙarfinsa, hankalinsa ya gama cika, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi hukunci da ilimi na annabta daga gare shi, domin yana cikin bayin Allah waɗanda suka kyautata ayyukan ibadarsu ga Allah, kuma irin wannan sakamako Allah yake yi wa irin waɗannan bayi nasa.
To a sakamakon wancan matsayi na annabta da ilimi da Allah ya ba wa Yusufu ne wannan jarabawar ta biyo baya. Watau uwar ɗakinsa wadda yake ƙarƙashinta ita ce ta neme shi da yin lalata da ita saboda irin kyan halitta da Allah ya yi masa a lokacin babu wani ɗa namiji da ya sami kamarta. Sai ta kukkulle ƙofofi ta yadda babu ta inda zai gudu, kuma babu wanda zai iya shigowa inda suke, don haka ko mene ne zai faru a nan babu wanda zai sani har ya ɗorar gaba. Sai ko ta shiga kiran sa tana neman ya matso jikinta. Annabi

Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai yi wata-wata ba ya mayar mata da amsa yana mai neman Allah ya tsare shi daga aikata wannan mummunan aiki, ya nuna mata cewa, yin haka cin amanar mai gidansa ne wanda ya kyautata masa iya kyautatawa, ya ɗauke shi a matsayin ɗansa ya yi masa duk abin da uba yake yi wa ɗansa; to ta yaya shi kuma zai saka masa da cin amanarsa? Idan har ya yi haka to ya tabbata azzalumi, don haka ba zai taɓa rabauta ba, domin azzalumai sam ba sa samun wani rabo. To amma duk da haka ba ta ƙyale shi ba, domin ta riga ta sa shi a ranta, shi ma abin ya fara ɗarsa masa a zuciya, to amma ya ga ayoyin Ubangijinsa waɗanda ba za su taɓa ƙyale shi har ya aikata irin wannan ɗanyen aiki ba. Allah ya kawar da shi daga aikata mummunan aiki da alfasha, saboda shi mutum ne da Allah ya tsarkake masa zuciya shi ma ya tsarkake ibadarsa ga Allah kaɗai.
Yayin da Yusufu ya fuskanci yadda matar nan ta dage a kan mummunar buƙatarta sai ya yi ƙoƙarin gudu ya nufi ƙofa a guje, ita kuma ta bi shi tare da ƙoƙarin kawo masa raruma har ta yaga masa riga ta baya. A daf da ƙofa ne suka yi kiciɓis da mijinta zai shigo. To nan da nan sai ta shirya makircin wanke kanta daga tuhuma, ta bayyana wa mijinta wai Yusufu ne ya neme ta da lalata, har ma nan take ta bayyana irin hukuncin da ya wajaba a yi masa, watau a ɗaure shi a kurkuku ko a gana masa mummunar azaba. Amma ba ta ambaci kisa ba domin tsananin son da take wa Yusufu. To a nan ne Annabi Yusufu shi ma ya fito ya kare kansa, ya faɗi gaskiyar abin da ya faru, ya bayyana cewa, ita ce ta neme shi, ba shi ne ya neme ta ba. Daga nan sai mai gidanta ya kasa tantance mai gaskiya a cikinsu, domin ba zai iya tuhumar Annabi Yusufu ba saboda ya san shi ya san kyawawan halayensa tun yana ƙarami. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nufi kawo wanda zai yi shaida daga cikin danginta wanda ya bayyana mai gaskiya a cikinsu, ya ce a duba rigar Yusufu a gani, idan ta gaba ta yage, to wannan alama ce da ke nuna shi ne ya kai mata farmaki ita kuma wajen kare kanta har ta yaga masa riga, don haka ita ce mai gaskiya. Idan kuwa ta baya ne rigar ta yage, to wannan alama ce da ke nuna ita ce ta kai masa cacuma shi kuwa ya juya yana neman tserewa har ta yaga masa riga ta baya, don haka a nan shi ne mai gaskiya. Ana duba rigar Annabi Yusufu kuwa sai aka ga ta baya ne ta yage, sai nan take mai gidan Yusufu ya tabbatar da shi ne mai gaskiya, wannan kawai wani makirci ne matar ta ƙulla masa, sai ya ce mata wannan makircinta ne don ta shirya wa Yusufu ƙazafi, domin mata suna da makirci ba ƙanƙani ba. Daga nan ya roƙi Annabi Yusufu da ya yi watsi da wannan maganar kada ya ɗaga ta ga kowa domin ya rufa wa iyalansa asiri. Ya juya wajen matar ita kuma ya umarce ta da ta tuba ga Allah a kan laifinta na neman Yusufu da ta yi da kuma ƙazafi da ta yi masa, ya ce mata lalle ta tabbata cikin masu laifi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ƙarshen al'amarin mazinaci kunyata a gari.

2. Tsegumin da ke yawo a gari cewa: "Matar Azizu (babban mutum) tana neman yaron gidanta, tsananin son sa ya kai har ƙoƙon zuciyarta...." Wannan magana tana ƙunshe da suka iri daban-daban kamar haka:
• Matan gari suna kiran ta da 'matar babban mutum', wanda yake nuna tana da miji kenan; laifin zinar matar aure kuwa ya fi na budurwa muni.
• Sun dangana ta da Azizu, wanda yake nufin babban mutum a gari, wanda hakan yana nuni ga cewa laifinta ya kai matuƙa a muni, kamarta bai dace a same ta da wannan badaƙala ba.
• Bawa ne take nema fa ba ɗa ba; wannan ma wani ƙasƙanci ne gare ta.
• Ko da a ce yaron gidanta ne wanda yake ƙarƙashinta ba bawa ba take nema da lalata, wannan ma shi kansa wani ƙarin abin kunya ne.
• Ita ce ma take neman sa da kanta, wannan ma wani abin kunya ne, kuma ya nuna ya fi ta kamun kai da tsare mutunci.
• Soyayyarsa ta yi tsanani a zuciyarta har tana neman kaita ga zautuwa, wannan ma wata ƙaranta ce ga mace mai matsayi irin nata.

3. Taka-tsantsan da faɗawa cikin soyayyar da za ta haifar da cutuwa.

4. A ɗabi'ar mutane sun san cewa mala'iku halittu ne masu kyan sura.

5. Mutanen ƙwarai duk sanda suka shiga tsanani sukan ƙara rusuna wa Allah da kusantarsa da neman agajinsa.

6. Kada mutum ya rudî kansa da cewa ya fi ƙarfin makircin mata, sai dai ya nemi tsarin Allah ya kuma guje wa hanyar da tarkonsu zai kama shi.

7. A cikin faɗar Annabi Yusufu: "Ya Ubangijina, kurkuku shi ya fi soyuwa a gare ni a kan abin da suke nema na da shi. Idan kuwa ba ka kawar mini da makircinsu ba to zan karkata gare su kuma in zama cikin jahilai," akwai darussa biyu a nan:
Na ɗaya: Fifita kurkuku da uƙuba a kan zunubai da saɓon Allah.
Na biyu: Roƙon Allah ya tabbatar da zuciya a kan addininsa da ɗa'a gare shi, idan kuwa ba haka ba to zuciya za ta karkata zuwa ga saɓon Allah, daga nan mutum ya zamanto cikin jahilai.

8. Yaɗa alfasha da kururuta ta yana ƙara ƙarfafa ta.

9. Duk mijin da ba zai iya riƙe ragamar matarsa ba, to haƙiƙa zai rasa daidaito a cikin al'amuransa, tubka da warwara za su yi yawa a rayuwarsa.

Suratu Yusuf (30-35)
*وَقَالَ نِسۡوَةٞ فِي ٱلۡمَدِينَةِ ٱمۡرَأَتُ ٱلۡعَزِيزِ تُرَٰوِدُ فَتَىٰهَا عَن نَّفۡسِهِۦۖ قَدۡ شَغَفَهَا حُبًّاۖ إِنَّا لَنَرَىٰهَا فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٣٠ فَلَمَّا سَمِعَتۡ بِمَكۡرِهِنَّ أَرۡسَلَتۡ إِلَيۡهِنَّ وَأَعۡتَدَتۡ لَهُنَّ مُتَّكَـٔٗا وَءَاتَتۡ كُلَّ وَٰحِدَةٖ مِّنۡهُنَّ سِكِّينٗا وَقَالَتِ ٱخۡرُجۡ عَلَيۡهِنَّۖ فَلَمَّا رَأَيۡنَهُۥٓ أَكۡبَرۡنَهُۥ وَقَطَّعۡنَ أَيۡدِيَهُنَّ وَقُلۡنَ حَٰشَ لِلَّهِ مَا هَٰذَا بَشَرًا إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا مَلَكٞ كَرِيمٞ ٣١ قَالَتۡ فَذَٰلِكُنَّ ٱلَّذِي لُمۡتُنَّنِي فِيهِۖ وَلَقَدۡ رَٰوَدتُّهُۥ عَن نَّفۡسِهِۦ فَٱسۡتَعۡصَمَۖ وَلَئِن لَّمۡ يَفۡعَلۡ مَآ ءَامُرُهُۥ لَيُسۡجَنَنَّ وَلَيَكُونٗا مِّنَ ٱلصَّٰغِرِينَ ٣٢ قَالَ رَبِّ ٱلسِّجۡنُ أَحَبُّ إِلَيَّ مِمَّا يَدۡعُونَنِيٓ إِلَيۡهِۖ وَإِلَّا تَصۡرِفۡ عَنِّي كَيۡدَهُنَّ أَصۡبُ إِلَيۡهِنَّ وَأَكُن مِّنَ ٱلۡجَٰهِلِينَ ٣٣ فَٱسۡتَجَابَ لَهُۥ رَبُّهُۥ فَصَرَفَ عَنۡهُ كَيۡدَهُنَّۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٣٤ ثُمَّ بَدَا لَهُم مِّنۢ بَعۡدِ مَا رَأَوُاْ ٱلۡأٓيَٰتِ لَيَسۡجُنُنَّهُۥ حَتَّىٰ حِينٖ ٣٥

30. Waɗansu mata kuma a cikin garin suka ce: "Matar Azizu tana neman yaron gidanta; tsananin son sa ya rufe mata zuciya; lalle mu dai muna ganin ta a kan kuskure mabayyani."

31. Lokacin da ta ji irin tsegungumansu, sai ta aika musu (da gayyata), ta kuma tanadar musu wurin zaman cin abinci, kuma ta bai wa kowacce ɗayarsu wuƙa, ta kuma ce (da Annabi Yusufu): "Fita ka gilma ta gabansu." Lokacin da suka gan shi sai suka girmama shi suka yanyanke hannayensu, suka kuma ce: "Tsarki ya tabbata ga Allah; ai wannan ba mutum ba ne; wannan babban mala'ika ne kawai!"

32. Ta ce: "To wannan shi ne wanda kuka zarge ni a kansa. Haƙiƙa kuma na neme shi sai ya ƙi yarda; Wallahi kuwa in bai aikata abin da na umarce shi ba, to za a sa shi kurkuku, kuma lalle zai zamanto cikin wulaƙantattu."

33. (Annabi Yusufu) Ya ce: "Ya Ubangijina, kurkuku shi ya fi soyuwa a gare ni kan abin da suke nema na da shi. Idan kuwa ba Ka ije mini makircinsu ba, to zan karkata gare su kuma in zama cikin jahilai."

34. To sai Ubangijinsa Ya amsa masa, sai Ya ije masa makircin nasu. Lalle Shi ne Mai ji kuma Masani.

35. Sannan bayan duk sun ga ayoyin (da suke wanke Yusufu daga zargi) sai suka ga dai cewa lalle gara su ɗaure shi har zuwa wani lokaci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, labarin Yusufu da matar Azizu ya cika garin Misra har ya kai kunnen matan manyan gari, suka haɗu suna gulmarta, suna mamakin a ce mace mai daraja da matsayi irin nata amma tana neman yaron gidanta; lalle sonsa ya shiga har cikin ƙoƙon zuciyarta, ta kasa danne shi, lalle a faɗarsu, tana kan babban kuskure. Duk kuwa suna wannan tsegunguma ne domin suna so su ma su ga Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su ga irin kyan halittar da Allah ya yi masa, shi ya sa suka shirya wannan makircin, don labari ya je kunnen matar Azizu, ta ji haushi ta ba su damar su gan shi. To lokacin da ta ji wannan suka da suke yi mata da gulmar da suke yi sai ta aika musu goron gayyata don su zo su ga Yusufu su kuma fahimci hanzarinta. Ta shirya musu wurin zama na alfarma wanda aka cika shi da shimfiɗu da matasan kai iri-iri, sannan ga abinci kala-kala, ciki har da waɗanda sai an yi amfani da wuƙa kafin a ci. Ta ba wa kowace mace wuƙa a hannunta don yanka abinci, sannan ta umarci Yusufu ya fito daga inda ta zaunar da shi ya gilma ta gaban waɗannan matan su ga irin tsananin kyansa da kwarjininsa da sheƙin da yake yi. Ai kuwa yana fitowa suka yi ido huɗu da shi sai suka kiɗime, suka ruɗe, suka shiga yayyanke hannayensu da wuƙaƙe suna tsammanin abinci suke yankawa saboda tsananin kiɗimewa, suka shiga tsarkake Allah mahaliccinsa, suka ce wannan ba mutum ne ba; wani malaʾika ne mai daraja.

Ya tabbata a hadisin Miʾirajin Annabi (ﷺ) cewa, ya wuce ta wajen Annabi Yusufu a sama ta uku, ya gan shi an ba shi rabin kyau. [Muslim #162].

Lokacin da suka tantance irin tsananin kyan da Allah ya ba Yusufu, su ma sai tsananin sonsa ya ratsa zukatansu har suka ɗimauce. To a nan ne matar Azizu ta nufi bayyana musu kyan halinsa wanda su ba su sani ba, ta bayyana musu a fili cewa, wannan shi ne yaron da suke zargin ta a kansa, kuma tabbas ita ce ta neme shi tun farko amma ya ƙi yarda da buƙatarta. Sannan a gabansu ta yi masa barazana cewa idan har bai aikata abin da ta nema daga wajensa ba, to tabbas sai an kai shi kurkuku an tsare, kuma sai ya ga wulaƙanci.
Daga nan sai waɗannan mata suka shiga roƙon sa da ya amsa wa uwar gidansa ya yi mata abin da take nema. Jin haka ya sa Annabi Yusufu ya shiga addu'a yana neman kariya daga Allah, yana faɗa wa Ubangiji cewa, ya gwammace a kai shi kurkuku a tsare a kan ya amince wa abin da suke roƙo a wajensa, ya roƙe shi da ya kawar masa da makircinsu don gudun kada ya faɗa cikin tarkonsu ya sami kansa cikin jahilai, waɗanda suke fifita jin daɗin duniya a kan na lahira.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ya karɓi addu'ar Yusufu, ya kawar masa da makircinsu, lalle Allah mai jin addu'o'in bayinsa ne, masanin halayen da suke ciki.

Bayan Allah ya kuɓutar da Yusufu daga wannan jarrabawar, labarinsa kuma duk ya bazu a cikin garin Misra, sai Azizu da mutanensa suka yanke shawarar su saka Yusufu a kurkuku duk kuwa da sun ga ayoyi da dalilai masu nuna ba shi da laifin komai, saboda kawai su ɓoye abin kunyar da matar Azizu ta tabka, domin idan ba a ganin Yusufu yana yawo to maganar za ta mutu. Sai suka ɗaure shi zuwa wani lokaci da ba su iyakance shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kamar yadda ake shigar da mutum kurkuku saboda ya yi laifi, to hakanan wani lokaci akan shigar da shi saboda gaskiyarsa, don haka ba duk wanda aka kai kurkuku ne yake mai laifi ba.

2. Halaccin ambaton kirkin mutum domin kamun ƙafa da shi a wurinsa.

3. Yana da kyau mai da'awa ya yi amfani da buƙatar da mutane suke nema a wurinsa domin isar musu da saƙon gaskiya da jan hankalinsu.

4. Gabatar da shimfiɗa domin jan hankalin mai sauraro da kwantar masa da rai.

5. Wajabcin bin tafarkin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) na kaɗaita Allah da bauta da nesantar shirka.

6. Ya kamata ga mai ilimi ya sanar da mutane ilimin da Allah ya ba shi, domin yin haka godiya ce ga ni'imar Allah.

7. Ba koyaushe ne bin abin da aka samu daga iyaye yake zama laifi ba.

8. Yana da kyau ga mai da'awa ya riƙa amfani da duk wata dama da ya samu wajen kiran mutane zuwa gaskiya.

9. Yana da kyau ga mai ilimi idan wani ya nemi amsar wata tambaya daga wajensa, ya gabatar masa da bayanin abin da yake ganin ya fi masa muhimmanci fiye da abin da yake tambaya a kansa.

10. Cikar ubudiyya ta Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wadda ta sanya shi mai kira zuwa ga Tauhidi duk kuwa da cewa yana cikin wani mawuyacin hali.

11. Ba a fassarar mafarki da ka ko shaci-faɗi, a'a, ana yi ne da ilimi da hujja.

12. Shaiɗan yakan mantar da mutum ayyukan alheri.

Suratu Yusuf (36-42)

وَدَخَلَ مَعَهُ ٱلسِّجۡنَ فَتَيَانِۖ قَالَ أَحَدُهُمَآ إِنِّيٓ أَرَىٰنِيٓ أَعۡصِرُ خَمۡرٗاۖ وَقَالَ ٱلۡأٓخَرُ إِنِّيٓ أَرَىٰنِيٓ أَحۡمِلُ فَوۡقَ رَأۡسِي خُبۡزٗا تَأۡكُلُ ٱلطَّيۡرُ مِنۡهُۖ نَبِّئۡنَا
بِتَأۡوِيلِهِۦٓۖ إِنَّا نَرَىٰكَ مِنَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٣٦ قَالَ لَا يَأۡتِيكُمَا طَعَامٞ تُرۡزَقَانِهِۦٓ إِلَّا نَبَّأۡتُكُمَا بِتَأۡوِيلِهِۦ قَبۡلَ أَن يَأۡتِيَكُمَاۚ ذَٰلِكُمَا مِمَّا عَلَّمَنِي رَبِّيٓۚ إِنِّي
تَرَكۡتُ مِلَّةَ قَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ كَٰفِرُونَ ٣٧ وَٱتَّبَعۡتُ مِلَّةَ ءَابَآءِيٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَۚ مَا كَانَ لَنَآ أَن نُّشۡرِكَ بِٱللَّهِ
مِن شَيۡءٖۚ ذَٰلِكَ مِن فَضۡلِ ٱللَّهِ عَلَيۡنَا وَعَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشۡكُرُونَ ٣٨ يَٰصَٰحِبَيِ ٱلسِّجۡنِ ءَأَرۡبَابٞ مُّتَفَرِّقُونَ خَيۡرٌ أَمِ ٱللَّهُ
ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّارُ ٣٩ مَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ أَسۡمَآءٗ سَمَّيۡتُمُوهَآ أَنتُمۡ وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلۡطَٰنٍۚ إِنِ ٱلۡحُكۡمُ إِلَّا لِلَّهِۚ أَمَرَ أَلَّا
تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٤٠ يَٰصَٰحِبَيِ ٱلسِّجۡنِ أَمَّآ أَحَدُكُمَا فَيَسۡقِي رَبَّهُۥ خَمۡرٗاۖ وَأَمَّا ٱلۡأٓخَرُ
فَيُصۡلَبُ فَتَأۡكُلُ ٱلطَّيۡرُ مِن رَّأۡسِهِۦۖ قُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ ٱلَّذِي فِيهِ تَسۡتَفۡتِيَانِ ٤١ وَقَالَ لِلَّذِي ظَنَّ أَنَّهُۥ نَاجٖ مِّنۡهُمَا ٱذۡكُرۡنِي عِندَ رَبِّكَ فَأَنسَىٰهُ
ٱلشَّيۡطَٰنُ ذِكۡرَ رَبِّهِۦ فَلَبِثَ فِي ٱلسِّجۡنِ بِضۡعَ سِنِينَ ٤٢ وَدَخَلَ مَعَهُ ٱلسِّجۡنَ فَتَيَانِۖ قَالَ أَحَدُهُمَآ إِنِّيٓ أَرَىٰنِيٓ أَعۡصِرُ خَمۡرٗاۖ وَقَالَ ٱلۡأٓخَرُ إِنِّيٓ أَرَىٰنِيٓ

أَحۡمِلُ فَوۡقَ رَأۡسِي خُبۡزٗا تَأۡكُلُ ٱلطَّيۡرُ مِنۡهُۖ نَبِّئۡنَا بِتَأۡوِيلِهِۦٓۖ إِنَّا نَرَىٰكَ مِنَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٣٦ قَالَ لَا يَأۡتِيكُمَا طَعَامٞ تُرۡزَقَانِهِۦٓ إِلَّا نَبَّأۡتُكُمَا بِتَأۡوِيلِهِۦ قَبۡلَ أَن يَأۡتِيَكُمَاۚ ذَٰلِكُمَا مِمَّا عَلَّمَنِي رَبِّيٓۚ إِنِّي تَرَكۡتُ مِلَّةَ قَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ كَٰفِرُونَ ٣٧ وَٱتَّبَعۡتُ مِلَّةَ ءَابَآءِيٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَۚ مَا كَانَ لَنَآ أَن نُّشۡرِكَ بِٱللَّهِ مِن شَيۡءٖۚ ذَٰلِكَ مِن فَضۡلِ ٱللَّهِ عَلَيۡنَا وَعَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشۡكُرُونَ ٣٨ يَٰصَٰحِبَيِ ٱلسِّجۡنِ ءَأَرۡبَابٞ مُّتَفَرِّقُونَ خَيۡرٌ أَمِ ٱللَّهُ ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّارُ ٣٩ مَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ أَسۡمَآءٗ سَمَّيۡتُمُوهَآ أَنتُمۡ وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلۡطَٰنٍۚ إِنِ ٱلۡحُكۡمُ إِلَّا لِلَّهِۚ أَمَرَ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٤٠ يَٰصَٰحِبَيِ ٱلسِّجۡنِ أَمَّآ أَحَدُكُمَا فَيَسۡقِي رَبَّهُۥ خَمۡرٗاۖ وَأَمَّا ٱلۡأٓخَرُ فَيُصۡلَبُ فَتَأۡكُلُ ٱلطَّيۡرُ مِن رَّأۡسِهِۦۚ قُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ ٱلَّذِي فِيهِ تَسۡتَفۡتِيَانِ ٤١ وَقَالَ لِلَّذِي ظَنَّ أَنَّهُۥ نَاجٖ مِّنۡهُمَا ٱذۡكُرۡنِي عِندَ رَبِّكَ فَأَنسَىٰهُ ٱلشَّيۡطَٰنُ ذِكۡرَ رَبِّهِۦ فَلَبِثَ فِي ٱلسِّجۡنِ بِضۡعَ سِنِينَ ٤٢

36. Wasu samari su biyu kuma suka shiga kurkukun tare da shi; ɗaya daga cikinsu ya ce: "Lalle na yi mafarki ina matsar giya." Ɗayan kuma ya ce: "Lalle na yi mafarki ina ɗauke da gurasa a kaina, tsuntsaye suna caccakar ta. Ba mu labarin fassararsa; lalle muna ganin ka kana cikin mutane nagari."

37. Ya ce: "Babu wani abinci da za a kawo muku sai na iya ba ku labarinsa tun ma kafin a kawo muku shi. Wannan yana daga abin da Ubangijina Ya sanar da ni; lalle ni na bar hanyar mutanen da ba sa ba da gaskiya da Allah, su kuma suna masu kafircewa da ranar lahira.

38. "Na kuma bi hanyar iyayena Ibrahimu da Is'haƙa da kuma Yaƙubu. Bai kamace mu ba a ce mu tara wani abu da Allah. Wannan yana daga falalar Allah a gare mu da kuma sauran mutane, sai dai kuma yawancin mutane ba sa godewa.

39. "Ya abokaina na kurkuku, yanzu iyayen giji barkatai su suka fi, ko kuwa Allah Ɗaya Mai rinjaye?

40. "Ba komai kuke bauta wa ba- bayan Allah- sai wasu sunaye da kuka ƙaga ku da iyayenku, waɗanda Allah bai saukar da wata hujja game da su ba. Hukunci na Allah ne kawai; Ya yi umarni cewa kada ku bauta wa kowa sai Shi kaɗai. Wannan shi ne addini miƙaƙƙe, sai dai yawancin mutane ba sa sanin (haka).

41. "Ya abokaina na kurkuku, amma ɗaya daga cikinku zai riƙa shayar da mai gidansa giya ne; amma ɗaya kuwa za a tsire shi ne, sannan tsuntsaye su zo su riƙa cakar kansa. An zartar da al'amarin da kuke fatawa game da shi."

42. Kuma ya ce wa wanda ya tabbatar da cewa shi zai tsira daga cikinsu: "Ka tuna wa mai gidanka ni;" sai Shaiɗan ya mantar da shi tuna wa mai gidan nasa, sai ya zauna a kurkuku 'yan shekaru.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) an kai shi kurkuku har kuma ya shahara wurin abokan zamansa a kurkuku da riƙon gaskiya da kyautatawa da amana da ilimin fassarar mafarki. To a kan haka ne wasu samari su biyu waɗanda suka shiga kurkuku tare da shi, har ma sun saba da shi, ɗayansu mai shayar da Sarki giya ne, na biyun kuwa mai dafa masa abinci ne. Sai mai shayar da Sarki ya ce wa Yusufu, shi ya yi mafarki yana matsar inabin giya, ɗayan kuwa ya ce shi ya yi mafarki yana ɗauke da gurasa a kansa, tsuntsaye suna tsattsaga, don haka suka roƙi Yusufu da ya taimaka ya fassara musu mafarkansu saboda sun kula shi mutumin kirki ne.
Ganin wannan dama ta samu ta sa Yusufu ya yi amfani da ita wajen kirawo su zuwa ga Tauhidi da barin shirka da Allah. Ya fara yi musu shimfiɗa da ba su labarin ni'imomin da Allah ya yi masa shi da iyayensa, ya nuna musu cewa, ban da sanin fassarar mafarki da ya yi, yana da wata baiwa da Allah ya yi masa, watau duk wani abinci da za a kawo musu, to yana iya ba su labarinsa tun kafin ya iso gare su, ya kuma sanar da

su cewa, wannan ilimin nasa daga Allah ne ba tsafi ko duba ba ne. Ya ci gaba da faɗa musu cewa, shi ya bar addinin mutanen da ba sa yin imani da Allah kuma suna kafirce wa ranar lahira, shi kuma ya bi addinin iyayensa ne annabawan Allah, Ibrahimu da Ishaƙa da Yaƙubu, shi ne addinin kaɗaita Allah da bauta, ya tabbatar musu da cewa bai dace a gare su ba su haɗa Allah da wani abu wajen bautarsa ko a siffofinsa, ya ce musu wannan falala ce da Allah ya yi musu, ya sanya su annabawa masu kira zuwa ga addininsa, da kuma mutane ta hanyar aiko musu da manzanni domin su karantar da su addinin gaskiya, to amma yawancin mutane ba sa yi wa Allah godiya a kan wannan babbar ni'ima sai dai su butulce masa su kama hanyar ƙarya.
To bayan Annabi Yusufu ya yi musu wannan shimfiɗar sai ya dawo kansu ya kirawo su zuwa ga Tauhidi da watsar da abubuwan da suke bauta wa ba Allah ba, ya kirawo su da abokan zamansa a kurkuku' domin su ƙara nutsuwa da shi, ya nuna musu cewa, yanzu waɗannan abubuwan bauta barkatai da suka riƙe waɗanda ba za su iya tsinana musu komai a rayuwarsu ba, kuma ba sa cutar da su ba sa iya amfanar su, yanzu su suka fi alheri gare su ko kuma Allah Ɗaya wanda ya siffantu da siffofi na kamala, wanda ba shi da abokin tarayya, kuma mai rinjaye a kan kowa da komai, wanda abin da ya ga dama shi ne yake wakana, wanda bai ga dama ba kuma ba zai wakana ba?
Ya ci gaba da bayyana musu cewa, ba komai suke bautawa ba sai wasu sunayen da su ne da iyayensu suka ƙirƙire su, babu wata hujja da suke da ita daga Allah a kan cewa waɗannan abubuwa alloli ne a bauta musu, domin kuwa hukunci na Allah ne shi kaɗai, ba nasu ba, ba kuma na iyayensu ba; shi ne kuma ya umarce su da kada su bauta wa kowa sai shi kaɗai. Annabi Yusufu ya tabbatar musu da cewa, waɗannan bayanai da suke ji daga bakinsa shi ne miƙaƙƙen addini, duk wani addinin da ba shi ba karkatacce ne, sai dai yawancin mutane ba su san haka ba, don haka suke bauta wa wasu ba Allah ba.
Bayan Annabi Yusufu ya gama yi musu wannan bayani sai kuma ya juyo kan maganar fassarar mafarkinsu, ya sake kiran su da 'abokan zamansa a kurkuku', ya faɗa musu cewa, wanda ya yi mafarki yana matsar inabin giya, to za a fitar da shi daga kurkuku, zai kuma koma aikinsa na shayar da Sarki giya. Amma wanda ya yi mafarkin yana ɗauke da gurasa a kansa tsuntsaye suna caccakar ta, to shi za a yanke masa hukuncin kisa a kuma gicciye shi har ya ruɓe tsuntsaye su riƙa caccakar naman kansa da ƙwaƙwalwarsa. Ya ce musu, wannan ita ce fatawar da suka nema wajensa, haka abin zai faru babu makawa.
Daga nan sai Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nemi wanda ya tabbatar shi ne zai kuɓuta ya koma aikinsa na gidan Sarki, idan ya kuɓuta to ya tayar wa da Sarki maganarsa ko zai sake bincike a kai har ya gano gaskiyar lamarin. To amma sai Shaiɗan ya mantar da wannan mutum ya tayar da maganar Annabi Yusufu a wurin Sarki, wannan ya jawo Annabi Yusufu ya ƙara wani adadin shekaru a cikin kurkuku.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mafarkin da sarki ya yi shi ne ya kawo ƙarshen zaman Yusufu a kurkuku, domin haka Allah ya shirya. An fito da shi ne don ya fassara wannan mafarkin mai ban mamaki, wanda fassararsa ta shafi ɗaukacin al'ummar ƙasar, domin an kasa samun mai iya fassarar sai shi Annabi Yusufu. Daga nan sai falalarsa da iliminsa suka bayyana ga kowa, ya kuma sami ƙarin matsayi a duniya da lahira.

2. Daga ni'imar da Allah ya yi wa Yusufu, shi ne ba a neme shi ya fassarra mafarkin Sarki ba sai bayan da Sarkin ya nemi manyan bokayensa da fadawansa su fassara amma suka kasa sannan ne Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fassara musu, domin Allah ya fito da matsayinsa ga Sarki da sauran mutanensa.

3. Kafiri zai iya yin mafarki kuma ya zama gaskiya. Amma kuma wanda ya fi kowa gaskiyar zance shi ne mafarkinsa ya fi zama gaskiya.

4. Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai tayar da zancen saƙon da ya yi wa saurayin nan ga Sarki ba, ballantana ma ya zarge shi da sakacin mantuwa, domin ya saddaƙar cewa haka Allah ya shirya ba zai fita daga kurkuku ba sai ya cika waʾadin da Allah ya dîbar masa.

5. Muhimmancin adana abinci domin fuskantar lokacin tsananin buƙata.

6. Yana da kyau mai ba da fatawa ya ƙara wa mai tambaya wani abin da yake da buƙatar sanin sa ko da bai yi tambaya a kansa ba.

7. Wanda aka tambaye shi abin da bai sani ba, to wajibi ne ya tambayo wanda ya sani.

8. Bayanin tasirin abokan shawara a kan masu mulki.

Suratu Yusuf (43-49)

وَقَالَ ٱلۡمَلِكُ إِنِّيٓ أَرَىٰ سَبۡعَ بَقَرَٰتٖ سِمَانٖ يَأۡكُلُهُنَّ سَبۡعٌ عِجَافٞ وَسَبۡعَ سُنۢبُلَٰتٍ خُضۡرٖ وَأُخَرَ يَابِسَٰتٖۖ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمَلَأُ أَفۡتُونِي فِي رُءۡيَٰيَ إِن كُنتُمۡ لِلرُّءۡيَا تَعۡبُرُونَ ٤٣ قَالُوٓاْ أَضۡغَٰثُ أَحۡلَٰمٖۖ وَمَا نَحۡنُ بِتَأۡوِيلِ ٱلۡأَحۡلَٰمِ بِعَٰلِمِينَ ٤٤ وَقَالَ ٱلَّذِي نَجَا مِنۡهُمَا وَٱدَّكَرَ بَعۡدَ أُمَّةٍ أَنَا۠ أُنَبِّئُكُم بِتَأۡوِيلِهِۦ فَأَرۡسِلُونِ ٤٥ يُوسُفُ أَيُّهَا ٱلصِّدِّيقُ أَفۡتِنَا فِي سَبۡعِ بَقَرَٰتٖ سِمَانٖ يَأۡكُلُهُنَّ سَبۡعٌ عِجَافٞ وَسَبۡعِ سُنۢبُلَٰتٍ خُضۡرٖ وَأُخَرَ يَابِسَٰتٖ لَّعَلِّيٓ أَرۡجِعُ إِلَى ٱلنَّاسِ لَعَلَّهُمۡ يَعۡلَمُونَ ٤٦ قَالَ تَزۡرَعُونَ سَبۡعَ سِنِينَ دَأَبٗا فَمَا حَصَدتُّمۡ فَذَرُوهُ فِي سُنۢبُلِهِۦٓ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّا تَأۡكُلُونَ ٤٧ ثُمَّ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ سَبۡعٞ شِدَادٞ يَأۡكُلۡنَ مَا قَدَّمۡتُمۡ لَهُنَّ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّا تُحۡصِنُونَ ٤٨ ثُمَّ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ عَامٞ فِيهِ يُغَاثُ ٱلنَّاسُ وَفِيهِ يَعۡصِرُونَ ٤٩ وَقَالَ ٱلۡمَلِكُ إِنِّيٓ أَرَىٰ سَبۡعَ بَقَرَٰتٖ سِمَانٖ يَأۡكُلُهُنَّ سَبۡعٌ عِجَافٞ وَسَبۡعَ سُنۢبُلَٰتٍ خُضۡرٖ وَأُخَرَ يَابِسَٰتٖۖ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمَلَأُ أَفۡتُونِي فِي رُءۡيَٰيَ إِن كُنتُمۡ لِلرُّءۡيَا تَعۡبُرُونَ ٤٣ قَالُوٓاْ أَضۡغَٰثُ أَحۡلَٰمٖۖ وَمَا نَحۡنُ بِتَأۡوِيلِ ٱلۡأَحۡلَٰمِ بِعَٰلِمِينَ ٤٤ وَقَالَ ٱلَّذِي نَجَا مِنۡهُمَا وَٱدَّكَرَ بَعۡدَ أُمَّةٍ أَنَا۠ أُنَبِّئُكُم بِتَأۡوِيلِهِۦ فَأَرۡسِلُونِ ٤٥ يُوسُفُ أَيُّهَا ٱلصِّدِّيقُ أَفۡتِنَا فِي سَبۡعِ بَقَرَٰتٖ سِمَانٖ يَأۡكُلُهُنَّ سَبۡعٌ عِجَافٞ وَسَبۡعِ سُنۢبُلَٰتٍ خُضۡرٖ وَأُخَرَ يَابِسَٰتٖ لَّعَلِّيٓ أَرۡجِعُ إِلَى ٱلنَّاسِ لَعَلَّهُمۡ يَعۡلَمُونَ ٤٦ قَالَ تَزۡرَعُونَ سَبۡعَ سِنِينَ دَأَبٗا فَمَا حَصَدتُّمۡ فَذَرُوهُ فِي سُنۢبُلِهِۦٓ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّا تَأۡكُلُونَ ٤٧ ثُمَّ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ سَبۡعٞ شِدَادٞ يَأۡكُلۡنَ مَا قَدَّمۡتُمۡ لَهُنَّ إِلَّا قَلِيلٗا مِّمَّا تُحۡصِنُونَ ٤٨ ثُمَّ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ عَامٞ فِيهِ يُغَاثُ ٱلنَّاسُ وَفِيهِ يَعۡصِرُونَ ٤٩

43. Sarki kuma ya ce (da jamaʾarsa): ‘‘Lalle na yi mafarkin shanu guda bakwai masu ƙiba da wasu bakwan ƙanjamammu suna cinye su da kuma zangarnu guda bakwai koraye da wasu bakwai busassu. Ya ku manyan malamai, ku sanar da ni fassarar mafarkin nan nawa in kun iya fassara mafarki.’’

44. Suka ce: ‘‘Ai (wannan) kwashe-kwashen mafarki ne (kawai); mu kuma ba masana fassarar mafarki ne ba.’’

45. Wanda kuwa ya tsiran nan daga cikinsu, ya kuma tuna bayan zamani mai tsawo, ya ce: ‘‘Ni zan ba ku labarin fassararsa; to ku aike ni.’’

46. (Ya zo kurkuku ya ce): ‘‘Ya Yusufu, ya mai riƙon gaskiya, ka ba mu fatawar (mafarki) game da shanu bakwai masu ƙiba ga wasu bakwan ƙanjamammu suna cinye su, da kuma zangarnu guda bakwai korayr da wasu bakwai busassu, don in koma wajen mutanen (da suka turo ni) saboda su sani.’’

47. (Annabi Yusufu) ya ce: ‘‘Za ku yi noma shekara bakwai a jere; to abin da kuka girba sai ku bar shi a zangarniyarsa, sai kaɗan daga abin da za ku ci.

48. ‘‘Sannan bayan wannan wasu (shekarun) bakwai masu tsanani za su zo su cinye abin da kuka tanada a cikinsu, sai ɗan kaɗan daga abin da kuke adanawa.

49. ‘‘Sannan kuma wata shekara za ta zo wadda a cikinta ne mutane za su sami ruwa, a cikinta ne kuma za su tatsi (abubuwan sha).’’

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana fassarar mafarkin da Sarkin Misra ya yi wanda ya zamanto shi ne sanadiyyar fitowar Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga kurkuku, ya kuma zama dalilin ɗaukakarsa a idon Sarki da jamaʾarsa.
Sarkin Misra ya yi mafarkin shanu masu ƙiba guda bakwai da kuma wasu guda bakwai ƙanjamammu, amma kuma su ne suke cinye masu ƙibar. Sannan ya ga wasu zangarnu koraye guda bakwai da wasu bakwai busassu; don haka sai ya tara bokayensa da manyan gari ya nemi su fassara masa wannan mafarkin nasa mai rikitarwa. To amma sai suka nuna masa cewa, wannan kawai kwashe-kwashen mafarkai ne waɗanda ba su da wata fassara, kuma su ma ba su da ilimin fassarar mafarkai.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa, saurayin nan wanda ya samu kuɓuta daga kurkuku, watau mai shayar da Sarki sai ya tuna da Annabi Yusufu bayan tsawon lokaci, sai ya je ya sami Sarki ya ce masa shi zai sanar da shi fassarar mafarkinsa bayan ya tambayo Yusufu idan Sarki ya yi masa izinin zuwa wajensa. Sarki ya ba shi izinin zuwa wurin Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya je ya kirawo shi da sunansa ya siffanta shi da mai yawan gaskiya, ya ba shi labarin mafarkin Sarki, ya roƙe shi ya fassara masa shi domin ya koma ya sanar da shi da jamaʾarsa.
Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ba da fassarar mafarkin Sarki tare da bayyana mafita game da matsalar da take tattare da shi, inda ya ce: Mutanen Misra za su yi shekara bakwai a jere suna noma cikin nasara, to duk abin da suka girbe a kowace shekara su bar shi cikin zangarniyarsa don kada ƙwari su lalata shi sai ɗan kaɗan wanda za su yi amfani da shi, shi ne za su sussuke. To bayan wucewar waɗannan shekaru bakwai masu yalwa ne za a kuma samu wasu shekaru bakwai na fari, a cikinsu mutane za su yi ta cinye abin da suka tara a waɗancan shekarun bakwai masu yalwa, ba za su bar komai ba sai abin da za su ɓoye na iri.
Bayan waɗannan shekarun na fari kuma sai wata shekara ta zo wadda a cikinta ne mutane za su sami ruwan sama mai yawa, shukokinsu su yi kyau matuƙa, mutane su sami abinci isasshe har ma da wanda za su riƙa tatsewa kamar inabi da zaitun da rake da makamantansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin ladabin Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kauce wa zargin matar Azizu kai-tsaye, sai kawai ya yi maganar matan gari masu yayyanke hannayensu. Ya yi haka ne domin rufin asiri ga matar da ta kyautata mazauninsa ta kula da shi lokacin da aka kawo shi gidanta, domin shi mai karamci ne ɗan mai karamci ɗan mai karamci ɗan Badaɗayin Allah.

2. Falalar riƙon gaskiya da muhimmancinta.

3. Halaccin mutumin da ake zargi ya yi ƙoƙarin wanke kansa daga tuhuma ta duk hanyar da ta dace.

4. Ran mutum yana daga cikin maƙiyansa don haka yake da buƙatar sa ido koyaushe.

5. Daga cikin hanyoyin samun gafarar Allah da rahamarsa akwai iƙirari da aikata laifi.

6. Yana daga cikin jarumta mutum ya bayyana laifinsa ya kuma yarda da kuskurensa.

7. Ƙwato wa wanda aka zalunta haƙƙinsa da taimakon sa da janyo mutum mai gaskiya da amana jiki ko da kuwa baƙo ne marar gata, wannan abu ne da ya kamata.

8. Halaccin mutum ya nemi wani muƙamin da zai taimaka wa al'umma idan ya kasance babu wanda ya cancanta sai shi kuma ya amince ba zai fitinu ba.

9. Shardanta ilimi da amana ga mutumin da za a danƙa wa shugabancin wani abu na al'umma.

10. Fifitar ilimi a kan kyawon sura: Annabi Yusufu kyan surarsa ya shigar da shi fitina da zaman gidan yari, amma iliminsa ya fito da shi ya kuma ɗaukaka matsayinsa a duk fadin ƙasar Misra.

11. Bayanin fifikon sakamakon lahira ga masu imani da taƙawa.

Suratu Yusuf (50-57

وَقَالَ ٱلۡمَلِكُ ٱئۡتُونِي بِهِۦۖ فَلَمَّا جَآءَهُ ٱلرَّسُولُ قَالَ ٱرۡجِعۡ إِلَىٰ رَبِّكَ فَسۡـَٔلۡهُ مَا بَالُ ٱلنِّسۡوَةِ ٱلَّٰتِي قَطَّعۡنَ أَيۡدِيَهُنَّۚ إِنَّ رَبِّي بِكَيۡدِهِنَّ عَلِيمٞ ٥٠ قَالَ مَا خَطۡبُكُنَّ إِذۡ رَٰوَدتُّنَّ يُوسُفَ عَن نَّفۡسِهِۦۚ قُلۡنَ حَٰشَ لِلَّهِ مَا عَلِمۡنَا عَلَيۡهِ مِن سُوٓءٖۚ قَالَتِ ٱمۡرَأَتُ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡـَٰٔنَ حَصۡحَصَ ٱلۡحَقُّ أَنَا۠ رَٰوَدتُّهُۥ عَن نَّفۡسِهِۦ وَإِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٥١ ذَٰلِكَ لِيَعۡلَمَ أَنِّي لَمۡ أَخُنۡهُ بِٱلۡغَيۡبِ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي كَيۡدَ ٱلۡخَآئِنِينَ ٥٢ ۞وَمَآ أُبَرِّئُ نَفۡسِيٓۚ إِنَّ ٱلنَّفۡسَ لَأَمَّارَةُۢ بِٱلسُّوٓءِ إِلَّا مَا رَحِمَ رَبِّيٓۚ إِنَّ رَبِّي غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٥٣ وَقَالَ ٱلۡمَلِكُ ٱئۡتُونِي بِهِۦٓ أَسۡتَخۡلِصۡهُ لِنَفۡسِيۖ فَلَمَّا كَلَّمَهُۥ قَالَ إِنَّكَ ٱلۡيَوۡمَ لَدَيۡنَا مَكِينٌ أَمِينٞ ٥٤ قَالَ ٱجۡعَلۡنِي عَلَىٰ خَزَآئِنِ ٱلۡأَرۡضِۖ إِنِّي حَفِيظٌ عَلِيمٞ ٥٥ وَكَذَٰلِكَ مَكَّنَّا لِيُوسُفَ فِي ٱلۡأَرۡضِ يَتَبَوَّأُ مِنۡهَا حَيۡثُ يَشَآءُۚ نُصِيبُ بِرَحۡمَتِنَا مَن نَّشَآءُۖ وَلَا نُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٥٦ وَلَأَجۡرُ ٱلۡأٓخِرَةِ خَيۡرٞ لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ٥٧

50. Sarki kuwa ya ce: "Ku zo min da shi." Lokacin da ɗan aiken ya zo masa (ya ce Sarki na kira), sai ya ce: "Koma wurin mai gidanka ka tambaye shi, mene ne halin matan da suka yanyanke hannaye nsu? Lalle Ubangijina Yana sane da makircinsu."

51. (Sarki) ya ce: "Mene ne labarinku lokacin da kuka nemi Yusufu da lalata?" Suka ce: "Tsarki ya tabbata ga Allah; ba mu san wani mummunan abu game da shi ba." Matar Azizu ta ce: "Yanzu kam gaskiya ta bayyana; ni ce da kaina na nemi lalata da shi; lalle kuma shi yana cikin masu gaskiya.

52. "Wannan kuwa don ya san cewa ni ban ha'ince shi a bayan idonsa, kuma lalle Allah ba Ya shiryar da makircin masu ha'inci.

53. "Ba kuma wai ina wanke kaina ba ne. Babu shakka ɗabi'ar rai ce ta umarci mutum da yin mummunan abu, sai fa wanda Ubangijina Ya yi wa jin ƙai. Lalle Ubangijina Mai gafara ne Mai jin ƙai."

54. Sarki kuma ya ce: "Ku zo min da shi in mai da shi ɗan-gaban-goshina." Lokacin da ya yi magana da shi sai ya ce: "Lalle kai kam a yau kana da matsayi (babba, kuma kai) amintacce ne a wurinmu!"

55. (Yusufu) Ya ce: "Ka naɗa ni mai kula da taskokin ƙasa, lalle ni mai kiyaye (amana) ne, masani."

56. Kamar haka ne Muka kafa Yusufu a bayan ƙasa; yana zama a cikinta inda ya ga dama. Muna bayar da rahamarmu ga wanda Muka ga dama, ba kuwa za Mu tozarta ladan masu kyautatawa ba.

57. Kuma lalle ladan lahira shi ya fi ga waɗanda suka yi imani kuma suka zamanto suna kiyaye dokokin (Allah).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana abin da ya biyo bayan fassarar mafarkin Sarki da Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi. Sarki ya yi matuƙar farin ciki da wannan fassarar har ma ya nemi a je a zo masa da Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). To lokacin da ɗan aike ya isar da kiran Sarki ga Annabi Yusufu sai ya nuna ba zai amsa wannan kiran ba har sai Sarki ya nemo matan da suka yi masa sharri har aka ɗaure shi, ya sake bincikar su game da wannan zargin, domin da man makirci ne suka shirya masa tare da goyon bayan matar Azizu, kuma Allah yana sane da wannan makirci nasu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Da ni ne na daɗe a kurkuku kamar yadda Yusufu ya daɗe to da na amsa kiran mai kira." Watau manzon Sarki. [Bukhari #3372 da Muslim #151].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) daga Manzon Allah (ﷺ) game da faɗar Allah: "Lokacin da ɗan aike ya zo masa sai ya ce: 'Ka koma wurin mai gidanka ka tambaye shi mene ne halin matan da suka yayyanke hannayensu? Lalle Ubangijina masani ne ga makircinsu." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Da ni ne shi da na amsa kira da gaggawa, da ban nemi yankan hanzari ba." [Ahmad #8554].

Da aka sanar da Sarki amsar Annabi Yusufu, sai ya sa aka tara masa waɗannan matan ya tambaye su labarinsu game da Yusufu lokacin da suka neme shi domin aikata lalata da shi. Nan take suka wanke Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga zargin da ake yi masa, suka tabbatar wa da Sarki cewa ba su taɓa sanin sa da wani mummunan abu ba. To a nan ne ita ma matar Azizu ta fito ta faɗi gaskiyar abin da ya faru tsakaninta da shi, cewa, ita ce da kanta ta nemi Yusufu, amma shi lalle yana cikin mutane masu gaskiya a duk lamurransa. Ta kuma ce ta yi wannan iƙirari ne a gaban Sarki don Yusufu ya san ba za ta ci amanarsa ba a bayan idonsa, domin Allah ba ya shiryar da makircin maciya amana.
Matar Azizu ta ƙara da cewa, wannan magana da take yi ba wai tana wanke kanta ne daga laifukan da ta aikata ba, lalle ta san cewa koyaushe rai yana umartar mutum da mummunan aiki ne, sai fa wanda Allah ya ji ƙan sa ya kuɓutar da shi, lalle kuma Allah Ubangiji mai gafara ne mai jin ƙai.
To bayan Sarki ya tabbatar da kuɓutar Annabi Yusufu daga duk wani zargi, ya fahimci cewa mutumin kirki ne mai ilimi da haƙuri, sai ya nemi a zo masa da shi domin ya mayar da shi na kusa da shi a fada. Aka zo da Yusufu gaban Sarki, yayin da ya yi magana da Sarki sai ya fahimci girman matsayinsa sai ya ce: "Lalle kai kam a yau kana da babban matsayi kuma amintacce a wurinmu."
Daga nan Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nemi a ɗora masa wani nauyi na taimakon al'umma, musamman ganin mawuyacin halin da za su faɗa nan gaba na yunwa saboda ƙarancin abinci, sai ya nemi a ba shi matsayin mai kula da taskokin arzikin ƙasar domin zai riƙe amana, kuma yana da ilimin kula da tattalin arziki.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, to kamar yadda ya kuɓutar da Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga kurkuku ya wanke shi daga zargin da ake yi masa, hakanan kuma ya kafa shi a cikin ƙasar Misra yana kai-komo a cikinta yadda ya ga dama; wannan kuma wata rahama ce daga Allah da yake yi wa wanda ya ga dama cikin bayinsa a nan duniya, kuma ba ya tozarta ladan masu kyautatawa, yana ba su sakamakonsu cikakke. Kuma lalle sakamakon da ya tanadar musu a lahira ya fi alheri ga waɗanda suka yi imani da Allah kuma suka kiyaye dokokinsa ta hanyar aiki da umarninsa da barin haninsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittar yaro takan yi saurin canzawa saɓanin halittar babba. A lokacin da ‘ya’uwan Yusufu suka jefa shi rijiya sun kasance manya ne, shi kuwa Yusufu a lokacin yaro ne ƙarami. Sannan wanda aka zalunta yakan riƙe kamannin wanda ya zalunce shi, ba kasafai yakan mance shi ba, saɓanin azzalumi nan da nan yake mance kamannin wanda ya zalunta.

2. Karamcin Annabi Yusufu da kyawawan halayensa, duk abin da ‘yan’uwansa suka yi masa bai hana shi kyautata musu ba.

3. Mai mulki yakan haɗa tsakanin kwaɗaitarwa da tsoratarwa, domin da haka ne abubuwa sukan daidaita.

Suratu Yusuf (58-62)
وَجَآءَ إِخۡوَةُ يُوسُفَ فَدَخَلُواْ عَلَيۡهِ فَعَرَفَهُمۡ وَهُمۡ لَهُۥ مُنكِرُونَ ٥٨ وَلَمَّا جَهَّزَهُم بِجَهَازِهِمۡ قَالَ ٱئۡتُونِي بِأَخٖ لَّكُم مِّنۡ أَبِيكُمۡۚ أَلَا تَرَوۡنَ أَنِّيٓ أُوفِي ٱلۡكَيۡلَ وَأَنَا۠ خَيۡرُ ٱلۡمُنزِلِينَ ٥٩ فَإِن لَّمۡ تَأۡتُونِي بِهِۦ فَلَا كَيۡلَ لَكُمۡ عِندِي وَلَا تَقۡرَبُونِ ٦٠ قَالُواْ سَنُرَٰوِدُ عَنۡهُ أَبَاهُ وَإِنَّا لَفَٰعِلُونَ ٦١ وَقَالَ لِفِتۡيَٰنِهِ ٱجۡعَلُواْ بِضَٰعَتَهُمۡ فِي رِحَالِهِمۡ لَعَلَّهُمۡ يَعۡرِفُونَهَآ إِذَا ٱنقَلَبُوٓاْ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِمۡ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٦٢

58. ‘Yan’uwan Yusufu kuma suka zo suka shiga wurinsa sai ya gane su, sai dai su ba su shaida shi ba.

59. Lokacin da ya haɗa musu kayan abincinsu, sai ya ce: “Ku zo min da ɗan’uwanku na wajen uba. Ashe ba kwa ganin irin yadda nake cika mudu, kuma ni ne mafi kyautata wa baƙi?

60. “To idan ba ku zo min da shi ba to fa ba ku da wani awo ke nan a wurina (nan gaba), kuma kada ma ku kusanto ni!”

61. Suka ce: “To za mu rarrashi babansa game da shi, kuma lalle tabbas za mu aikata (haka).”

62. (Yusufu) Ya ce da yaransa: “Ku sanya hajarsu cikin jakunkunansu don su gan ta lokacin da suka koma ga iyalinsu watakila za su dawo.”

Lokacin da Yusufu ya karɓi matsayin mai kula da taskokin arzikin ƙasar Misra, ya tafiyar da aikinsa yadda ya kamata: an shuke gonakin ƙasar Misra, an yi noma an sami amfanin gona mai yawa a shekarun nan bakwai masu yalwa, aka kuma cika rumbuna da hatsi domin fuskantar shekaru bakwai na fari. Lokacin da aka fara fari wanda ya shafi kowane yanki har da ƙasar Falasdinu inda Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ‘ya’yansa suke rayuwa, sai Yaƙubu ya aiko ‘ya’yansa zuwa Misra domin su nemo abinci.
A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin da ‘yan’uwan Yusuf suka shiga wurinsa sai ya gane su, amma su ba su gane shi ba saboda kamanninsa sun canza bayan shekaru da ya kwashe ba ya tare da su, domin sun jefa shi rijiya ne tun yana ƙarami. To lokacin da ya yi musu awo kamar yadda yake yi wa kowa, domin a tsarinsa babu wanda ake ba shi fiye da kayan rakumi ɗaya, sai ya tambaye su labarin gidansu, sai suka faɗa masa suna da ɗan’uwa na wajen uba, sai ya nemi su zo masa da shi duk sanda za su dawo zai ƙara musu kayan rakumi ɗaya, ya ce ba su ga yadda yake cika musu mudu ba kuma da irin karɓar baƙin da ya yi musu? Ya kuma tsoratar da su cewa, idan ba su dawo da wannan ɗan’uwan nasu ba, to sun tabbata makaryata don haka ba zai ƙara yi musu awo ba, kada ma su matso kusa da inda yake, watau kar su sake shigo masa ƙasa. Sai suka amsa wa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa za su nemi babansu ya ba su dama su zo da shi, za su kuma yi iya ƙoƙarinsu a kan haka ba za su yi ƙasa a gwiwa ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya umarci ma'aikatansa da su mayar wa da 'yan'uwansa hajarsu a cikin kayansu domin idan sun koma ƙasarsu su gan ta su fahimci ba ciniki ya yi da su ba, wannan zai sa su dawo tare da ɗan'uwansu, domin su nuna wa Yusufu cewa lalle su mutane ne masu gaskiya, don haka zai karɓi hajjarsu ya sayar musu da abincin da suka zo nema.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba a cutar mumini ta kafa ɗaya sau biyu.

2. Yin taka-tsantsan cikin al'amura ta hanyar ƙarfafa yarjejeniya da rantsuwa mai ƙarfi.

3. Tuhuma idan da akwai ƙwararan dalilai ba laifi ne ba.

4. Neman tsari daga kambun baka domin shi gaskiya ne.

5. Gargaɗin Musulmi game da abin da zai cutar da shi da nuna masa abin da ya fi masa alheri yana daga cikin nasiha a addini.

6. Koyar da 'ya'ya yin riƙo da sabubba na zahiri tare da dogara ga Allah shi kaɗai.

7. Amfanin yin biyayya ga iyaye da ɗaukar nasihunsu da kyawawan shawarwarinsu ga 'ya'yansu.

Suratu Yusuf (63-68)

فَلَمَّا رَجَعُوٓاْ إِلَىٰٓ أَبِيهِمۡ قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا مُنِعَ مِنَّا ٱلۡكَيۡلُ فَأَرۡسِلۡ مَعَنَآ أَخَانَا نَكۡتَلۡ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ٦٣ قَالَ هَلۡ ءَامَنُكُمۡ عَلَيۡهِ إِلَّا كَمَآ أَمِنتُكُمۡ عَلَىٰٓ أَخِيهِ مِن قَبۡلُۖ فَٱللَّهُ خَيۡرٌ حَٰفِظٗاۖ وَهُوَ أَرۡحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ٦٤ وَلَمَّا فَتَحُواْ مَتَٰعَهُمۡ وَجَدُواْ بِضَٰعَتَهُمۡ رُدَّتۡ إِلَيۡهِمۡۖ قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا مَا نَبۡغِيۖ هَٰذِهِۦ بِضَٰعَتُنَا رُدَّتۡ إِلَيۡنَاۖ وَنَمِيرُ أَهۡلَنَا وَنَحۡفَظُ أَخَانَا وَنَزۡدَادُ كَيۡلَ بَعِيرٖۖ ذَٰلِكَ كَيۡلٞ يَسِيرٞ ٦٥ قَالَ لَنۡ أُرۡسِلَهُۥ مَعَكُمۡ حَتَّىٰ تُؤۡتُونِ مَوۡثِقٗا مِّنَ ٱللَّهِ لَتَأۡتُنَّنِي بِهِۦٓ إِلَّآ أَن يُحَاطَ بِكُمۡۖ فَلَمَّآ ءَاتَوۡهُ مَوۡثِقَهُمۡ قَالَ ٱللَّهُ عَلَىٰ مَا نَقُولُ وَكِيلٞ ٦٦ وَقَالَ يَٰبَنِيَّ لَا تَدۡخُلُواْ مِنۢ بَابٖ وَٰحِدٖ وَٱدۡخُلُواْ مِنۡ أَبۡوَٰبٖ مُّتَفَرِّقَةٖۖ وَمَآ أُغۡنِي عَنكُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن شَيۡءٍۖ إِنِ ٱلۡحُكۡمُ إِلَّا لِلَّهِۖ عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُۖ وَعَلَيۡهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُتَوَكِّلُونَ ٦٧ وَلَمَّا دَخَلُواْ مِنۡ حَيۡثُ أَمَرَهُمۡ أَبُوهُم مَّا كَانَ يُغۡنِي عَنۡهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن شَيۡءٍ إِلَّا حَاجَةٗ فِي نَفۡسِ يَعۡقُوبَ قَضَىٰهَاۚ وَإِنَّهُۥ لَذُو عِلۡمٖ لِّمَا عَلَّمۡنَٰهُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٦٨

63. Lokacin da suka dawo wurin babansu sai suka ce: "Ya babanmu, an hana mu yin awo (nan gaba), sai ka aika mu tare da ɗan'uwanmu mu yiwo awo, lalle kuma mu tabbas za mu kula da shi."

64. Ya ce: "Yanzu anya kuwa na amince muku game da shi, ai sai dai kawai kamar yadda na amince muku game da ɗan'uwansa tun tuni; sai dai Allah ne Fiyayen Mai kiyayewa, kuma Shi ne Fiyayyen masu rahama."

65. Lokacin kuma da suka buɗe jakunkunansu sai suka samu hajarsu an mayar musu da ita, suka ce: "Ya babanmu, me kuma muke nema? Ai wannan hajarmu ce aka dawo mana da ita; (idan muka koma) ai za mu nemo wa iyalinmu abinci kuma mu kula da ɗan'uwanmu, kuma mu ƙara kayan raƙumi (ɗaya). Wannan (kuwa) kaya ne sassauƙa."

66. (Babansu) Ya ce: “Ba zan aika ku tare da shi ba, har sai kun yi min alƙawari tsakaninku da Allah lalle za ku dawo min da shi, sai dai in wata masifa ta rutsa da ku.” Lokacin da suka yi masa alƙawari sai ya ce: “Allah ne Wakili a kan abin da muke faɗa.”

67. Ya kuma ce: “Ya ‘ya’yana, kada ku shiga (Masar) ta ƙofa guda; ku shiga ta ƙofofi daban-daban. Ba zan kare muku komai daga Allah ba; ba wani hukunci sai na Allah; a gare Shi na dogara, kuma a gare Shi ne masu dogaro ya wajaba su dogara.”

68. To lokacin da suka shiga ta inda babansu ya umarce su, (wannan) ba zai maganta musu komai ba daga Allah, sai dai wata buƙata ce a zuciyar Yakubu da ya samu biyanta. Lalle kuma shi tabbas mai ilimi ne na abin da Muka sanar da shi, sai dai yawancin mutane ba su sani ba.

A waɗannan ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da ya faru ne lokacin da ‘yan‘uwan Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka koma wurin babansu, suka ba shi labarin irin karamcin da Yusufu ya yi musu, kuma suka faɗa masa cewa, daga yanzu an ce ba za a ƙara yi musu awo ba idan ba su koma tare da ɗan’uwansu ba, don haka suka roƙi babansu da ya bar shi su tafi tare da shi domin su sami ƙarin awo, kuma suka yi alƙawarin lalle za su kula da shi ba abin da zai same shi har su koma gida. Sai Annabi Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana musu cewa, ba zai taɓa sakin jiki ya amince da maganarsu ba bayan kuwa bai mance da abin da suka yi wa Yusufu a baya ba. Domin kuwa ya amince musu akan Yusufu ne bayan sun yi masa alƙawarin kula da shi, amma ba su cika wancan alƙawari ba, don haka ba zai aminta da su ba, dogaronsa kaɗai ga Allah yake, shi ne Fiyayyen mai kiyayewa kuma Fiyayyen masu rahama.
Sai kuma bayan sun buɗe kayayyakinsu sai suka ga hajarsu an dawo musu da ita, watau an ba su kayan abincin ne kyauta ba a karɓi komai daga wajensu ba. Don haka suka ce wa babansu, me kuma za su nema a wajen wannan babban mutum bayan irin wannan goma ta arziki da ya yi musu!? Ga shi dai ya dawo musu da tamanin da suka zo da shi, don haka wannan ya ƙara musu ƙarfin gwiwar lalle su koma masa da ɗan’uwansu domin su sake yin awon abinci ga iyalansu, su kuma kula da ɗan’uwansu, sannan kuma ga ƙarin kayan raƙumi ɗaya na ɗan’uwansu, wannan kuwa abu ne mai sauƙi a wurin Azizu, watau Yusufu, ya yi musu wannan karamci.
To amma mahaifinsu Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) har yanzu bai nutsu da maganganun ‘ya’yansa nasa ba, domin bai manta baya ba, sai ya ce ba zai tura dan’uwansu tare da su ba har sai sun ɗauki alƙawari mai ƙarfi tsakaninsu da Allah na cewa za su dawo da shi gida sai dai in wani abu ne ya faru wanda ya fi ƙarfinsu ya hana su dawo da shi. To bayan sun yi masa alƙawari tsakaninsu da Allah a kan haka, sai ya ce, Allah ne wakili a kan abin da suka faɗa.
Sai kuma Annabi Yaƙubu ya yi wa ‘ya’yansa wasiyya cewa, idan sun isa ƙasar Misra, to kada su shiga gaba ɗayansu ta ƙofa guda; su shiga ta ƙofofi daban-daban domin kauce wa wata cutarwa da za ta iya fuskantar su, don kada ta same su gaba ɗayansu a lokaci guda. Ya kuma tabbatar musu cewa, ba yana faɗa musu haka ba ne domin ko zai iya kare su daga wani abin cutarwa da Allah ya yi nufin ya same su ba, ko ya jawo musu wani amfani da Allah bai nufe su da shi ba; babu abin da yake faruwa sai abin da Allah ya hukunta faruwarsa. Ya tabbatar musu cewa, shi ma ga Allah kaɗai ya dogara, don haka gare shi kaɗai duk masu dogara za su dogara.
Da yawa daga cikin malaman tafsiri sun bayyana cewa, abin da Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake jiye wa ‘ya’yansa tsoro shi ne kambun baka, saboda kasancewarsu dukkansu mazaje ne masu kyan halitta, sannan suna sanye da tufafi iri ɗaya waɗanda ba irin na Misra ba. Kuma da an gan su za a gane baƙi ne. Sai ya ji tsoron kambun baka ya same su, domin ya san kambun baka gaskiya ne (kamar yadda ya zo a hadisi). [Dubi Bukhari #5740 da Muslim #5830].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin amfani da dabara domin ƙwato wani haƙƙi ba tare da cutar da wani ba.

2. Halaccin sanya lada ga wanda ya taimaka wajen gano wani ɓataccen abu.

3. Halaccin kafa hujja da kyawawan halayen mutum don bayyana kuɓutarsa daga abin da ake tuhumarsa a kai.

4. Sunna ce ta Allah mai ɗorewa ya ɗaukaka ma'abocin ilimi a kowane lokaci. Idan Allah ya so bawansa sai ya arzuta shi da ilimi da fahimta.

5. Ilimi teku ne wanda ba shi da gaci, mutum yana ƙara shiga cikinsa yana ƙara gane zurfinsa.

6. Abu ne mai matuƙar kyau ga wanda yake jagorancin al'umma ya nisanci ramuwar gayya, domin duk wanda Allah ya ɗora alhakin jama'a a wuyansa to zai yi ta haɗuwa da suka da zargi saboda al'umma cike take da jahilai da miyagu, idan ya saba wa kansa da ɗaukar fansar duk wani abu na rashin kyautatawa da za a yi masa, to duk lokacinsa zai tafi ne wajen ramuwa da ɗaukar fansa maimakon yi wa al'ummarsa aiki don Allah.

7. Tsufa yana da wani haƙƙi na musamman da masu hankali ke la'akari da shi a koyaushe.

8. Yin magana mai harshen damo wata hanya ce ta kauce wa faɗawa cikin ƙarya.

Suratu Yusuf (69-79)

وَلَمَّا دَخَلُواْ عَلَىٰ يُوسُفَ ءَاوَىٰٓ إِلَيۡهِ أَخَاهُۖ قَالَ إِنِّيٓ أَنَا۠ أَخُوكَ فَلَا تَبۡتَئِسۡ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٦٩ فَلَمَّا جَهَّزَهُم بِجَهَازِهِمۡ جَعَلَ ٱلسِّقَايَةَ فِي رَحۡلِ أَخِيهِ ثُمَّ أَذَّنَ مُؤَذِّنٌ أَيَّتُهَا ٱلۡعِيرُ إِنَّكُمۡ لَسَٰرِقُونَ ٧٠ قَالُواْ وَأَقۡبَلُواْ عَلَيۡهِم مَّاذَا تَفۡقِدُونَ ٧١ قَالُواْ نَفۡقِدُ صُوَاعَ ٱلۡمَلِكِ وَلِمَن جَآءَ بِهِۦ حِمۡلُ بَعِيرٖ وَأَنَا۠ بِهِۦ زَعِيمٞ ٧٢ قَالُواْ تَٱللَّهِ لَقَدۡ عَلِمۡتُم مَّا جِئۡنَا لِنُفۡسِدَ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا كُنَّا سَٰرِقِينَ ٧٣ قَالُواْ فَمَا جَزَٰٓؤُهُۥٓ إِن كُنتُمۡ كَٰذِبِينَ ٧٤ قَالُواْ جَزَٰٓؤُهُۥ مَن وُجِدَ فِي رَحۡلِهِۦ فَهُوَ جَزَٰٓؤُهُۥۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلظَّٰلِمِينَ ٧٥ فَبَدَأَ بِأَوۡعِيَتِهِمۡ قَبۡلَ وِعَآءِ أَخِيهِ ثُمَّ ٱسۡتَخۡرَجَهَا مِن وِعَآءِ أَخِيهِۚ كَذَٰلِكَ كِدۡنَا لِيُوسُفَۖ مَا كَانَ لِيَأۡخُذَ أَخَاهُ فِي دِينِ ٱلۡمَلِكِ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُۚ نَرۡفَعُ دَرَجَٰتٖ مَّن نَّشَآءُۗ وَفَوۡقَ كُلِّ ذِي عِلۡمٍ عَلِيمٞ ٧٦ ۞قَالُوٓاْ إِن يَسۡرِقۡ فَقَدۡ سَرَقَ أَخٞ لَّهُۥ مِن قَبۡلُۚ فَأَسَرَّهَا يُوسُفُ فِي نَفۡسِهِۦ وَلَمۡ يُبۡدِهَا لَهُمۡۚ قَالَ أَنتُمۡ شَرّٞ مَّكَانٗاۖ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا تَصِفُونَ ٧٧ قَالُواْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡعَزِيزُ إِنَّ لَهُۥٓ أَبٗا شَيۡخٗا كَبِيرٗا فَخُذۡ أَحَدَنَا مَكَانَهُۥٓۖ إِنَّا نَرَىٰكَ مِنَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٧٨ قَالَ مَعَاذَ ٱللَّهِ أَن نَّأۡخُذَ إِلَّا مَن وَجَدۡنَا مَتَٰعَنَا عِندَهُۥٓ إِنَّآ إِذٗا لَّظَٰلِمُونَ ٧٩

69. Lokacin kuma da suka shiga wurin Yusufu sai ya janye ɗan'uwansa wajensa ya ce: "Ni fa lalle ɗan'uwanka ne; saboda haka kada ka damu da abin da suke aikatawa."

70. To lokacin da (Azizu) ya haɗa musu kayayyakinsu sai ya sanya ma'aunin a cikin kayan ɗan'uwansa, sannan mai shela ya yi yekuwa da cewa: "Ya ku waɗannan ayari, lalle ku fa tabbas ɓarayi ne!"

71. Suka ce: (yayin da) suka juyo wajensu: "Wane abu ne ya ɓace muku?"

72. Suka ce: "Ma'aunin Sarki ne ba mu gani ba, kuma duk wanda ya zo da shi yana da ladan kayan raƙumi guda, kuma ni ne mai lamuninsa."

73. Suka ce: “Wallahi haƙiƙa kun sani ba mu zo don mu yi ɓarna a bayan ƙasa ba, kuma mu ba mu taɓa zama ɓarayi ba.”

74. (Mutanen Sarki) suka ce: “Mene ne horon da za a yi masa (ɓarawon) idan ƙarya kuke yi?”

75. Suka ce: “Horonsa shi ne, wanda aka same shi a cikin kayansa, to shi ne horonsa (watau a riƙe shi). Kamar haka muke saka wa azzalumai.”

76. Sai ya fara da (binciken) jakunkunansu kafin jakar ɗan’uwansa; sannan ya fito da shi (mudun) daga jakar ɗan’uwansa. Kamar haka Muka shirya wa Yusufu; ba zai yiwu ya riƙe ɗan’uwansa ba a shari’ar Sarkin (Masar), sai dai idan Allah Ya ga dama. Muna ɗaukaka darajojin waɗanda Muka ga dama ne. Kuma duk wani mai ilimi akwai wanda yake samansa a ilimi.

77. Suka ce: “Idan har ya yi sata, to haƙiƙa ɗan’uwansa ma a da can ya taɓa yin sata.” Sai Yusufu ya ɓoye wannan (maganar) a ransa bai kuma bayyana musu ita ba, yana mai cewa (a ransa): “Ku ne dai masu mummunan matsayi (a wurin Allah). Allah kuwa Shi ne Mafi sanin abin da kuke sifantawa.”

78. Suka ce: “Ya kai wannan Azizu, lalle yana da mahaifi tsoho tukuf, sai ka riƙe ɗayanmu a madadinsa; lalle kuwa muna ganin kana daga masu kyautatawa.”

79. Ya ce: “Allah Ya kiyaye mu da riƙe wani ba wanda muka sami kayanmu a wurinsa ba; idan kuwa muka yi haka to lalle mun zama azzalumai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ‘yan’uwan Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun zo masa tare da ɗan’uwansa kamar yadda suka yi masa alƙawari. Da shigarsu sai Yusufu ya yi ƙoƙarin ya janye dan’uwansa shaƙiƙi wajensa ya kuma nuna masa cikin sirri cewa shi ne Yusufu ɗan’uwansa, ya labarta masa duk abin da ya wakana a baya tsakaninsa da ‘yan’uwansa ya umarce shi da kada ya bayyana wannan sirri ga ‘yan’uwansa, kuma kada ya ji wata damuwa ta tsoron ko za su cutar da shi kamar yadda suka yi wa Yusufu a can baya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin da Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sa yaransa suka haɗa wa ‘yan’uwansa kayyayakinsu suka ɗora musu a kan raƙumansu, sai ya umarce su da su sanya ma’aunin Sarki wanda ake yin awon da shi cikin kayan ɗan’uwansa shaƙiƙi ba tare da sauran ‘yan’uwansa sun sani ba, da nufin shirya wata dabara da zai riƙe ɗan’uwansa a wurinsa. Bayan sun kama hanya sun tafi, sai Yusufu ya aika mai shela ya bi bayansu yana shelanta dakatar da su domin sun yi sata. Jin an kira su barayi sai abin ya ɗaure musu kai, sai duk suka juyo wajen mai shela suna tambayar sa mene ne ya ɓace musu shi da mutanensa suka fito nema? Sai suka ce, ai ma’aunin Sarki ne ya ɓace ake neman sa, kuma har an sanya lada ga wanda ya gano shi, watau za a ba shi kayan raƙumi guda, kuma shi mai wannan shelar ya ƙara tabbatar musu da cewa, shi ne lamuni a kan haka.
Daga nan ‘yan’uwan Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka yi rantsuwa a kan cewa, su ba su zo wannan gari don su yi sata ba, kuma su tun da suke ba su taɓa yin sata ba.

Sai mai shela da jama’arsa suka ce musu: “To wane irin horo za a yi wa wanda aka same shi da wannan laifi na sata a yadda yake a shari’ar ƙasarku?” Sai suka ce ai a shari’arsu duk wanda aka gano kayan sata a wurinsa to ana miƙa shi ne ga hannun wanda ya yi wa satar ya mayar da shi bawansa. Haka ne hukuncin ɓarayi a ƙasarsu.

Daga nan sai suka mayar da su wajen Yusufu don yin bincike, sai ya fara da binciken jakunkunan ‘yan’uwansa kafin ya binciki jakar ɗan’uwansa shaƙiƙi domin kada su fahimci dabarar da ya shirya musu. Da ya bincika jakar ɗan’uwansa sai ya fito da ma’aunin Sarki daga cikinta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, kamar yadda ya shirya masa ya sanya ma’aunin Sarki cikin jakar ɗan’uwansa, hakanan ya shirya masa yadda zai hukunta ɗan’uwansa da shari’ar ƙasarsu, kuma ya zamanto su ne da kansu suka yanke wannan hukuncin domin ba su taɓa tsammanin za a sami wannan ma’auni a cikin kayansu ba. Ba don wannan dabarar da Allah ya shirya wa Yusufu ba, to da babu yadda zai iya riƙe ɗan’uwansa a wurinsa, domin ƙasar Misra ba ta tanadi haka ba, sai dai idan Allah ya ga dama ta wata hanyar daban, kuma shi mai iko ne a kan haka. Allah ya bayyana cewa, yana ɗaga matsayin wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, kuma komai zurfin ilimin mutum to akwai wanda ya fi shi; ilimin Allah kuwa ya fi na kowa.
Ganin abu ya kasance haka, ga su ana ganin su sun fito daga babban gida sai suka nuna wa Yusufu cewa, ai wannan ba abin mamaki ne Binyaminu ya yi sata ba, domin a can baya ma ɗan’uwansa shaƙiƙi, suna nufin Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), shi ma ya taɓa yin sata, don haka wannan halin ‘yan ɗakinsu ne, amma su ba halinsu ne yin sata ba.
Annabi Yusufu da ya ji wannan suka da aka yi gare shi da ɗan’uwansa daga bakinsu sai ya ɓoye damuwarsa a ransa, ya danne fushinsa bai nuna musu shi ba ko a fuska ballatana har ya ɗauki wani matakin ramuwar gayya. A ransa kawai ya ce su dai ne masu mummunan matsayi a wurin Allah kuma Allah ne mafi sanin abin da suke siffanta su da shi na sata, domin ya san Annabi Yusufu da ɗan’uwansa ba ɓarayi ne ba.
Bayan hukuncin riƙe ɗan’uwansu ya tabbata sai suka shiga lallashin Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suna nuna masa cewa, shi wannan ɗan’uwansu da zai riƙe shi a matsayin bawa babansa tsoho ne tukuf kuma zai shiga damuwar rabuwa da ɗansa da yake matuƙar ƙauna, don haka ya yi musu alfarma ya riƙe ɗaya daga cikinsu a madadinsa, domin sun lura da cewa shi Yusufu mutumin kirki ne. To amma sai Yusufu ya nuna musu cewa bai dace ba ya bar wanda aka sami kaya a wurinsa a riƙe wanda bai yi laifi ba, idan ya yi haka to ya yi zalunci, shi kuwa adalin mai mulki ne ba azzalumi ba.
Abin lura a maganar Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne bai ce: “Wanda ya yi sata ba” sai ya ce: “Wanda muka sami kayanmu a wurinsa” don gudun kada ya yi ƙarya, domin ɗan’uwansa bai yi sata ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin yin kyakkyawan haƙuri wanda babu raki da koka wa wanin Allah a cikinsa.

2. Duk sanda al’amari ya tsananta, to a lokacin aka fi sa ran samun sauƙi.

3. Mumini ba ya fitar da ƙauna daga samun sauƙi na Ubangiji duk kuwa yadda al’amari ya tsananta.

4. Furta damuwa ba da nufin koka wa wanin Allah ba, wannan ba ya kore haƙuri da dangana.

5. Kuka da hawaye saboda wata damuwa ko ɓacin rai bai saɓa wa dogaro ga Allah da sallama wa ƙaddarar Allah ba.

6. Bawa ya koka wa Allah halin damuwar da yake ciki bai saɓa wa haƙuri ba.

7. Kyakkyawan fata daga Allah shi yake ƙara sa bawa ƙoƙari da kazar-kazar a kan abin da yake fatan samu, amma yanke ƙauna da fitar da rai shi yake haifar da mutuwar zuciya da rashin karsashi.

8. Fitar da ƙauna daga rahamar Allah yana daga cikin manyan laifuka.

Suratu Yusuf (80-87)

فَلَمَّا ٱسْتَيْـَٔسُواْ مِنْهُ خَلَصُواْ نَجِيًّا ۖ قَالَ كَبِيرُهُمْ أَلَمْ تَعْلَمُوٓاْ أَنَّ أَبَاكُمْ قَدْ أَخَذَ عَلَيْكُم مَّوْثِقًا مِّنَ ٱللَّهِ وَمِن قَبْلُ مَا فَرَّطتُمْ فِى يُوسُفَ ۖ فَلَنْ أَبْرَحَ ٱلْأَرْضَ حَتَّىٰ يَأْذَنَ لِىٓ أَبِىٓ أَوْ يَحْكُمَ ٱللَّهُ لِى ۖ وَهُوَ خَيْرُ ٱلْحَـٰكِمِينَ ﴿٨٠﴾ ٱرْجِعُوٓاْ إِلَىٰٓ أَبِيكُمْ فَقُولُواْ يَـٰٓأَبَانَآ إِنَّ ٱبْنَكَ سَرَقَ وَمَا شَهِدْنَآ إِلَّا بِمَا عَلِمْنَا وَمَا كُنَّا لِلْغَيْبِ حَـٰفِظِينَ ﴿٨١﴾ وَسْـَٔلِ ٱلْقَرْيَةَ ٱلَّتِى كُنَّا فِيهَا وَٱلْعِيرَ ٱلَّتِىٓ أَقْبَلْنَا فِيهَا ۖ وَإِنَّا لَصَـٰدِقُونَ ﴿٨٢﴾ قَالَ بَلْ سَوَّلَتْ لَكُمْ أَنفُسُكُمْ أَمْرًا ۖ فَصَبْرٌ جَمِيلٌ ۖ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَأْتِيَنِى بِهِمْ جَمِيعًا ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٨٣﴾ وَتَوَلَّىٰ عَنْهُمْ وَقَالَ يَـٰٓأَسَفَىٰ عَلَىٰ يُوسُفَ وَٱبْيَضَّتْ عَيْنَاهُ مِنَ ٱلْحُزْنِ فَهُوَ كَظِيمٌ ﴿٨٤﴾ قَالُواْ تَٱللَّهِ تَفْتَؤُا۟ تَذْكُرُ يُوسُفَ حَتَّىٰ تَكُونَ حَرَضًا أَوْ تَكُونَ مِنَ ٱلْهَـٰلِكِينَ ﴿٨٥﴾ قَالَ إِنَّمَآ أَشْكُواْ بَثِّى وَحُزْنِىٓ إِلَى ٱللَّهِ وَأَعْلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٨٦﴾ يَـٰبَنِىَّ ٱذْهَبُواْ فَتَحَسَّسُواْ مِن يُوسُفَ وَأَخِيهِ وَلَا تَاْيْـَٔسُواْ مِن رَّوْحِ ٱللَّهِ ۖ إِنَّهُۥ لَا يَاْيْـَٔسُ مِن رَّوْحِ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلْكَـٰفِرُونَ ﴿٨٧﴾

80. To lokacin da suka fitar da rai daga gare shi, sai suka kaɓe suna ganawa. Babbansu ya ce: “Ba ku san cewa babanku ya ɗauki alƙawari daga gare ku tsakaninku da Allah ba, kuma a da can ga irin sakacin da kuka yi game da Yusufu? To ni dai ba zan bar ƙasar (Masar) ba har sai babana ya yi min izini (da komawa), ko kuwa Allah Ya hukunta (abin da Ya ga dama) da ni; Shi ne kuwa Fiyayyen masu hukunci.

81. “Sai ku koma wurin babanku ku ce da shi: “Ya babanmu, lalle ɗanka ya yi sata! Ba mu kuwa ba da shaida ba sai da abin da muka sani, ba mu kuma zamanto masu kiyaye gaibu ba.

82. “Kuma ka tambayi mutanen alƙaryar da muka kasance a cikinta (watau Masar) da kuma ayarin da muka zo cikinsu. Wallahi mu kam lalle masu gaskiya ne.”

83. Ya ce: “Ba haka ba ne, zuciyarku dai ta shirya muku wani abu. Haƙuri kawai shi ya fi kyau (gare ni). Ina sa tsammani Allah Ya kawo min su gaba ɗaya. Lalle Shi ne Masani, Mai hikima.”

84. Sai ya kau da kai daga gare su, ya kuma ce: “Wayyo baƙin cikina game da Yusufu!” Idanuwansa kuwa suka yi fari don baƙin ciki, yana cike da ɓacin rai.

85. Suka ce: “Wallahi ba za ka bar tuna Yusufu ba har sai ka tasam ma mutuwa ko sai ka zamanto cikin matattu!”

86. Ya ce: “Ni fa kawai ina bayyana tsananin damuwata ne da baƙin cikina ga Allah, kuma ina sane da abin da ba ku sani ba game da Allah.

87. “Ya ku ‘ya’yana, ku tafi ku lalubo labarin Yusufu shi da ɗan’uwansa, kada ku ɗebe ƙauna daga rahamar Allah. Lalle ba mai ɗebe ƙauna daga rahamar Allah sai mutane kafirai.”

A waɗannan ayoyi Allah ya bayyana cewa, yayin da ‘yan’uwan Yusufu suka ga ya ƙi yarda ya riƙe ɗaya daga cikinsu a madadin ɗan’uwansu Binyaminu sai suka kaɓe wuri guda suka shiga shawarar abin da ya kamata su yi, sai babbansu ya tuna musu rantsuwar da suka yi wa mahaifinsu da alƙawarin da suka ɗauka na cewa za su dawo da ɗan’uwansu Binyaminu kuma ba za su bari wani abin ƙi ya same shi ba sai dai abin da ya fi ƙarfinsu. Sannan ya sake tunatar da su abin da suka yi wa Yusufu sanda suka jefa shi rijiya da niyyar ɓatar da shi bayan sun yi wa mahaifinsu alƙawarin za su dawo da shi gida. Don haka shi kam ba zai iya yin arba da mahaifinsa a cikin irin wannan hali ba, shi dai zai ci gaba da zama a ƙasar Misra sai fa idan shi mahaifin

nasu ne ya yi masa izinin dawowa, ko kuma Allah ya zartar da hukuncinsa a kansa ya karɓo ɗan'uwansa ko kuma mutuwa ta riske shi a nan. Allah shi ne Fiyayyen masu hukunci, hukuncinsa kuwa adalci ne.
Daga nan sai ya shawarce su da su koma wurin mahaifinsu su shaida masa cewa, ɗansa Binyaminu ya yi sata kuma an yanke masa hukuncin zaman bauta a wurin wanda ya yi wa satar, kuma wannan maganar da suke faɗa masa iya gaskiyarsu ke nan, domin a gaban idonsu aka fito da ma'aunin Sarki daga jakar ɗan'uwansu, kuma su ba su san yana sata ba, domin da a ce sun sani to da ba su ɗaukar masa alƙawarin za su dawo da shi ba.
Bugu da ƙari kuma suka shaida masa cewa, idan yana shakkar wannan batu nasu, to ya aika a tambayo masa mutanen ƙasar Misra da kuma ayarin fataken da suka kasance tare a can don su tabbatar masa da gaskiyar labarin da ya ji daga bakinsu, domin dai su sun tabbatar suna da gaskiya.
Da suka koma ƙasarsu wajen mahaifinsu suka shaida masa abin da ya faru, amma shi bai gamsu ba sai kawai ya zarge su da cewa, zukatansu ne suka ƙawata musu wani makirci kamar yadda suka yi wa ɗan'uwansa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), don haka babu wani abu da zai iya yi sai dai kyakkyawan haƙuri wanda babu raki a cikinsa ko ya kai kukansa ga wani ba Allah ba. Amma kuma duk da haka bai fitar da rai cewa Allah zai dawo masa da 'ya'yansa ukun gaba ɗayansu komai daɗewa ba. Ya tabbatar da cewa, abin da yake ƙara masa ƙarfin gwiwar wannan fata nasa shi ne kasancewar Allah masanin komai ne kuma mai hikima ne cikin ayyukansa gaba ɗaya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, daga nan sai Yuƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kawar da kai daga 'ya'yan nasa, yana mai nuna wa Allah shi kaɗai damuwarsa da baƙin cikinsa game da rasa samun labarin ɗansa Yusufu. Ya yi matsanancin kuka da har ta kai baƙin da yake cikin idanunsa ya koma fari fat kamar ya yi yana, ƙirjinsa yana maƙare da fushi saboda yadda yake ɓoye wa mutane halin damuwar da yake ciki, har 'ya'yansa suka fara jin tsoron kada wannan damuwar da yake ciki ta zama sanadiyyar halakarsa, suka fara rarrashin sa kan ya rage yawan tunanin Yusufu don ya sawwaƙe wa kansa. To amma sai ya amsa musu da cewa, shi ga Allah kaɗai yake kai kukan tsananin damuwarsa da baƙin cikinsa, kuma ya san abin da su ba su sani ba game da tausayin Allah da luɗufinsa ga bayinsa yayin da suke cikin damuwa idan sun roƙe shi.
Daga nan sai ya sake umartar 'ya'yansa da su tafi su ci gaba da laluben labarin Yusufu da ɗan'uwansa, kada su cire tsammanin samun rahamar Allah da yaye damuwar bayinsa, domin babu wanda yake cire tsammani daga samun rahamar Allah da taimakonsa sai mutane kafirai waɗanda ba su san girman Ƙudurar Allah ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin mutum ya ba da labarin halin da ya shiga na talauci ko rashin lafiya da makamantansu ga wanda yake tsammanin zai iya taimaka masa.

2. Allah yakan jarrabi annabawa da tsanani ko da yalwa.

3. Tabbatar faruwar abin da Allah ya sanar da Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da yake cikin rijiya na cewa sai ya ba wa 'yan'uwansa labarin abin da suka yi masa ba tare da sun san da hakan ba.

4. Babu mai saɓa wa Allah sai jahili, ma'ana, mumini yana auka wa saɓon Allah ne lokacin da sanin girman Allah da halarto da uƙubarsa ya ɓace daga zuciyarsa.

5. Ya halatta ga bawa ya ba da labarin ni'imomin da Allah ya yi masa, kamar yadda Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ba da labarin baiwa da tsoron Allah da haƙuri da ya ni'imta shi da su. Yin haka yana daga godiya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Ta hanyar tsoron Allah da haƙuri, bawa yakan samu matsayi a duniya da lahira.

7. Yana daga cikin kyawawan halayen mumini yin tuba ga Allah yayin da ya aikata wani laifi da yin iƙirari da laifinsa da neman afuwar wanda ya munana wa.

8. Karɓar hanzarin mai laifi da yafiya gare shi tare da kauce wa ramuwa ko ma zarginsa a kan abin da ya riga ya wuce.

9. Kamar yadda Allah yake ƙaddara samun waraka ta sababai da aka fi sani na magunguna da makamantansu, to hakanan yakan ba da waraka ta wasu hanyoyi da shi kaɗai ya san su. A yayin da rigar Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ta kasance ita ce mafarin shigar Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cikin damuwa da tashin hankali wanda har ya kai shi ga rasa ganinsa, to hakanan ita ce ta zama sanadiyyar fitarsa daga damuwa da dawowar ganinsa.

10. Jefa rigar Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a fuskar mahaifinsa ganinsa ya dawo yana daga cikin mu'ujizojinsa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Suratu Yusuf (88-93)

فَلَمَّا دَخَلُواْ عَلَيۡهِ قَالُواْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡعَزِيزُ مَسَّنَا وَأَهۡلَنَا ٱلضُّرُّ وَجِئۡنَا بِبِضَٰعَةٖ مُّزۡجَىٰةٖ فَأَوۡفِ لَنَا ٱلۡكَيۡلَ وَتَصَدَّقۡ عَلَيۡنَآۖ إِنَّ ٱللَّهَ يَجۡزِي ٱلۡمُتَصَدِّقِينَ ٨٨ قَالَ هَلۡ عَلِمۡتُم مَّا فَعَلۡتُم بِيُوسُفَ وَأَخِيهِ إِذۡ أَنتُمۡ جَٰهِلُونَ ٨٩ قَالُوٓاْ أَءِنَّكَ لَأَنتَ يُوسُفُۖ قَالَ أَنَا۠ يُوسُفُ وَهَٰذَآ أَخِيۖ قَدۡ مَنَّ ٱللَّهُ عَلَيۡنَآۖ إِنَّهُۥ مَن يَتَّقِ وَيَصۡبِرۡ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٩٠ قَالُواْ تَٱللَّهِ لَقَدۡ ءَاثَرَكَ ٱللَّهُ عَلَيۡنَا وَإِن كُنَّا لَخَٰطِـِٔينَ ٩١ قَالَ لَا تَثۡرِيبَ عَلَيۡكُمُ ٱلۡيَوۡمَۖ يَغۡفِرُ ٱللَّهُ لَكُمۡۖ وَهُوَ أَرۡحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ٩٢ ٱذۡهَبُواْ بِقَمِيصِي هَٰذَا فَأَلۡقُوهُ عَلَىٰ وَجۡهِ أَبِي يَأۡتِ بَصِيرٗا وَأۡتُونِي بِأَهۡلِكُمۡ أَجۡمَعِينَ ٩٣

88. Lokacin da suka shiga wurinsa (Annabi Yusufu) sai suka ce: "Ya Azizu, muna fama da yunwa mu mu da iyalanmu, kuma mun zo maka da wata haja marar daraja; to ka cika mana mudu, ka kuma kyautata mana; lalle Allah Yana saka wa masu kyautatawa."

89. Ya ce: "Shin kun kuwa san abin da kuka aikata wa Yusufu shi da ɗan'uwansa a lokacin da kuke jahilai?"

90. Suka ce: "Shin kuwa tabbas ko kai ne Yusufu ne?" Ya ce: "Ni ne Yusufu, wannan kuma ɗan'uwana ne; haƙiƙa Allah Ya yi mana baiwa; lalle wanda ya kiyaye dokokin (Allah) ya kuma yi haƙuri, to tabbas Allah ba Ya tozarta sakamakon masu kyautatawa."

91. Suka ce: "Wallahi haƙiƙa Allah Ya fifita ka a kanmu, mu kuma lalle mun tabbata masu kuskure!"

92. Ya ce: "A yau babu wani zargi a kanku; Allah zai yafe muku, Shi ne Mafificin masu rahama.

93. "Ku tafi da rigata wannan sannan ku jefa ta a fuskar babana, zai dawo mai gani, ku kuma zo min da iyalanku gaba ɗaya."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa, 'yan'uwan Annabi Yusufu sun fita nemansa shi da ɗan'uwanasa. Lokacin da suka shiga wurin Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai suka sanar da shi cewa, yanzu fa suna cikin wahalar yunwa da fari su da iyalinsu, kuma ga shi ba su da isasshen kuɗin musaya da za su sayi abinci mai yawa da shi wanda zai ishe su har da iyalinsu, suka kuma roƙe shi da ya taimaka musu ya karɓi ɗan abin da yake hannunsu ya cika musu mudu kamar yadda ya saba

yi musu a baya, ya ƙara da yi musu sadaka wajen karɓar hajarsu marar daraja, ko kuma ya ƙara musu a kan yadda yake ba su a baya domin Allah yana saka wa masu sadaƙa.
To a nan ne fa Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tausaya musu ya bayyana kansa ga ‘yan’uwansa bayan ya ji irin matsanancin halin da suka shiga na fari da yunwa da talauci, ya tambaye su ko sun tuna da makircin da suka ƙulla wa Yusufu shi da ɗan’uwansa da nuna ƙiyayya da hassada lokacin da suke cikin jahilci da rashin sanin abin da aikinsu zai haifar a gaba!?
Wannan magana ta Yusufu sai ta ɗaure wa ‘yan’uwansa kai domin ba su taɓa kawowa a tunaninsu ba cewa za su haɗu da Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cikin wannan ɗaukaka da girman matsayi, ga shi tsawon shekara biyu suna mu’amala da shi irin ta mabuƙaci da mai taimaka masa amma ba su gane shi ba, shi kuma bai nuna kansa gare su ba sai yanzu. Don haka cike da mamaki suka tambaye shi wai da gaske shi ne Yusufu? Ya kuma amsa da cewa, lalle shi ne Yusufu, wannan kuma ɗan’uwansa ne, ga shi Allah ya yi musu baiwa ya haɗa fuskokinsu bayan tsawon shekaru da rabuwa da juna. Sannan ya nuna musu cewa, haka sha’anin Allah yake, duk wanda ya tsare dokokin Allah ya yi aiki da umarninsa ya guje wa haninsa, ya kuma yi haƙuri a kan duk wata jarraba, to Allah ba zai taɓa tozarta masa kyawawan ayyukan nan nasa ba, zai kuma kare shi daga duk wani sharri da makirci.
To daga nan ne fa ‘yan’uwan Yusufu suka fara ba shi haƙuri da neman afuwa daga wurinsa, suka tabbatar masa tare da rantsuwa da Allah cewa, shi ne gaba da su domin Allah ya fifita shi a kansu da kyawawan ɗabi’unsa ga kuma sarauta da annabci duka Allah ya ba shi, sannan suka fito fili suka yarda da kuskuren da suka tabka a baya na nuna hassada da ƙiyayya gare shi da ɗan’uwansa.
To amma da yake Annabi Yusufu mai karamci ne ɗan mai karamci sai ya nuna musu cewa, babu sauran wani zargi a kansu, ya ma roƙa musu gafarar Allah da rahamarsa domin shi ne Fiyayyen masu jin ƙai.
To bayan Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana kansa ga ‘yan’uwansa ya kuma sami labarin mahaifinsu da halin da yake ciki na rashin gani, sai ya ba su rigarsa ya umarce su da su koma wajensa su jefa masa ita a fuskarsa ganinsa zai dawo ras, ya kuma nemi da su kwaso duk ilahirin mutanen gidansu gaba ɗaya su zo da su Misra.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Komai daɗewar tsanani kada ka fitar da ƙaunar samun sauƙi.

2. Duk girman laifi idan an ƙiyasta shi da rahamar Allah, to bai zama komai ba. ‘Yan’uwan Yusufu sun kalli girman laifinsu, don haka suka roƙi mahaifinsu ya nema musu gafara, shi kuma ya kalli girman rahamar Allah sai ya ambace ta bai ambaci laifinsu ba.

3. Halaccin neman addu’ar salihi.

4. Farkon matakin tuba na gaskiya shi ne yarda da laifin da aka yi.

5. Babban abin lura a rayuwar bawa shi ne kyakkyawan ƙarshensa, ba mummunan farkonsa ba. ‘Yan’uwan Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun yi mummunan aikin da suka yi a farkon al’amarinsu, amma daga ƙarshe sai suka yi tuba ta gaskiya suka kuma sami cikakkiyar afuwar Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kyakkyawar addu’ar mahaifinsu gare su.

Suratu Yusuf (94-98)

وَلَمَّا فَصَلَتِ ٱلۡعِيرُ قَالَ أَبُوهُمۡ إِنِّي لَأَجِدُ رِيحَ يُوسُفَۖ لَوۡلَآ أَن تُفَنِّدُونِ ٩٤ قَالُواْ تَٱللَّهِ إِنَّكَ لَفِي ضَلَٰلِكَ ٱلۡقَدِيمِ ٩٥ فَلَمَّآ أَن جَآءَ ٱلۡبَشِيرُ أَلۡقَىٰهُ عَلَىٰ وَجۡهِهِۦ فَٱرۡتَدَّ بَصِيرٗاۖ قَالَ أَلَمۡ أَقُل لَّكُمۡ إِنِّيٓ أَعۡلَمُ مِنَ ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٩٦ قَالُواْ يَٰٓأَبَانَا ٱسۡتَغۡفِرۡ لَنَا ذُنُوبَنَآ إِنَّا كُنَّا خَٰطِـِٔينَ ٩٧ قَالَ سَوۡفَ أَسۡتَغۡفِرُ لَكُمۡ رَبِّيٓۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٩٨

94. Lokacin da ayarin ya baro (Masar) sai babansu ya ce: "Lalle ina jin ƙanshin Yusufu; ba don dai kada ku ce na susuce ba!"

95. Suka ce: "Wallahi mun tabbata ba shakka (har yanzu) kana nan cikin daɗaɗɗìyar rikicewar nan taka!"

96. To lokacin da mai albishir ya zo masa sai ya jefa ta (rigar) a fuskarsa, sai ya dawo yana gani. Ya ce: "Ban gaya muku ba cewa lalle ni na san abin da ku ba ku sani ba game da Allah?"

97. Suka ce: "Ya babanmu, ka nema mana gafarar zunubanmu, lalle mun zamanto masu kuskure!"

98. Ya ce: "Ba da daɗewa ba zan nema muku gafarar Ubangijina; lalle Shi ne Mai yawan gafara, Mai jin ƙai."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya labarta lokacin da 'yan'uwan Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka baro Misra suka nufo ƙasarsu sai Annabi Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya faɗa wa 'ya'yansa da waɗanda suke tare da shi cewa, shi fa yana jiyo ƙamshin Yusufu ba don kar su ce ya susuce shi ya sa yake maganganu irin waɗannan ba. Amma wasu daga cikin 'ya'yansa suka ce da shi, har yanzu dai yana nan cikin daɗaɗɗìyar ɗìmuwarsa ta rashin Yusufu. Sai kuwa abin da ya zata shi ne ya faru. To lokacin da mai albishir ya zo wa Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai ya jefa masa rigar Yusufu a fuskarsa, nan take kuwa ganinsa ya dawo, sai ya ce da 'ya'yan nasa masu cewa ya kiɗìme cewa, ba ya faɗa musu cewa ya san luɗufin Allah da tausayinsa ga bayinsa abin da su ba su sani ba? To daga nan fa 'yan'uwan Yusufu suka fito fili suka tabbatar da laifinsu da suka yi, suka kuma roƙi mahaifinsu ya nema musu gafara wajen Allah don ya yafe musu. Sai ya amsa musu da cewa, zai nema musu gafarar Allah domin ya yafe musu saboda shi mai gafara ne ga bayinsa mai jin ƙansu ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Biyayya ga iyaye da girmama su.

2. Shaiɗan ne mai ɓata tsakanin 'yan'uwa har ya sa su yanke zumuntar da ke tsakaninsu.

3. Durƙuso domin gaisuwa al'ada ce ta mutanen Misra a da can, Musulunci ya musanya ta da sallama da musafaha.

4. Yayin da aka yi wa mutum laifi kuma ya yafe, to ya kamata kar ya tayar da maganar don nuna tabbacin ya yi afuwa.

5. Duk matsayin da mutum ya samu na duniya ko na lahira to ya sani wannan wata falala ce da Allah ya yi masa.

6. Yana da kyau mutum ya roƙi Allah kyakkyawar cikawa da haɗuwa da mutanen kirki a Aljanna.

فَلَمَّا دَخَلُواْ عَلَىٰ يُوسُفَ ءَاوَىٰٓ إِلَيۡهِ أَبَوَيۡهِ وَقَالَ ٱدۡخُلُواْ مِصۡرَ إِن شَآءَ ٱللَّهُ ءَامِنِينَ ٩٩ وَرَفَعَ أَبَوَيۡهِ عَلَى ٱلۡعَرۡشِ وَخَرُّواْ لَهُۥ سُجَّدٗاۖ وَقَالَ يَٰٓأَبَتِ هَٰذَا تَأۡوِيلُ رُءۡيَيَ مِن قَبۡلُ قَدۡ جَعَلَهَا رَبِّي حَقّٗاۖ وَقَدۡ أَحۡسَنَ بِيٓ إِذۡ أَخۡرَجَنِي مِنَ ٱلسِّجۡنِ وَجَآءَ بِكُم مِّنَ ٱلۡبَدۡوِ مِنۢ بَعۡدِ أَن نَّزَغَ ٱلشَّيۡطَٰنُ بَيۡنِي وَبَيۡنَ إِخۡوَتِيٓۚ إِنَّ رَبِّي لَطِيفٞ لِّمَا يَشَآءُۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡحَكِيمُ ١٠٠

99. Lokacin da suka shiga wurin Yusufu sai ya jawo iyayensa ya kuma ce: “Ku shigo Masar in Allah Ya ga dama kuna amintattu.”

100. Ya kuma ɗora mahaifansa a kan gadon mulki, suka kuma faɗi suna masu gaisuwa a gare shi, ya kuma ce: “Ya babanmu, wannan shi ne fassarar mafarkina na tun tuni. Lalle Ubangijina Ya mai da shi gaskiya; haƙiƙa kuma Ya kyautata min lokacin da Ya fitar da ni daga kurkuku, Ya kuma zo da ku daga ƙauye bayan Shaiɗan ya shiga tsakanina da ‘yan’uwana. Lalle Ubangijina Mai tausasawa ne ga wanda Ya ga dama. Lalle Shi ne Masani, Mai hikima.

101. “Ya Ubangijina, haƙiƙa Ka ba ni wani abu na mulki, Ka kuma sanar da ni wani abu daga fassarar mafarki; Ya Mahaliccin sammai da ƙasa, Kai ne Majiɓincina a duniya da lahira; ka karɓi raina ina Musulmi, Ka kuma haɗa ni da (mutane) salihai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ‘yan’uwan Yusufu su goma sha ɗaya da mahaifinsu Yaƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da sauran mutanen gidansu sun bar ƙasarsu ta Falasɗinu sun nufi ƙasar Misra kamar yadda Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nemi su yi. Lokacin da suka isa Misra suka shiga wurin Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai ya jawo iyayensa jikinsa ya yi musu goma ta arziki, ya girmama su matuƙa, ya kuma ce wa ‘yan’uwansa da sauran mutanen gidansu su shigo ƙasar Misra suna amintattu daga duk wani abin ƙi ko sharri, sannan kuma ya ɗora iyayensa a kan karagar mulkinsa. Su kuma sauran ‘yan’uwansa su goma sha ɗaya suka faɗi gabansa suka gaishe shi. To a nan ne Annabi Yusufu ya faɗa wa mahaifinsa cewa, wannan shi ne fassarar mafarkinsa da ya taɓa yi a baya na ganin rana da wata da taurari goma sha ɗaya suna yi masa sujjada, ga shi a yau Allah ya tabbatar da abin ya faru da gaske.
Daga wannan lokacin sai Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga godiya ga Allah bisa ga ni’imomin da ya yi masa masu yawa; daga cikinsu ya ambaci fito da shi daga kurkuku ba tare da an same shi da wani laifi ba da kuma sake haɗa shi da iyayensa da ‘yan’uwansa bayan tsawon shekaru ba sa tare da kuma rabo su da ƙauye su dawo birni da zama tare da shi bayan Shaiɗan ya shiga tsakaninsa da ‘yan’uwansa. Abin lura a nan shi ne, Annabi Yusufu bai ambaci laifin da ‘yan’uwansa suka yi masa ba, sai kawai ma ya nuna Shaiɗan ne ya shiga tsakaninsu, watau duk ya ɗora wa Shaiɗan laifin. Ya yi haka ne kuwa don ya tabbatar musu da cewa ya riga ya yafe musu ya kuma manta da duk abin da ya faru a tsakaninsu a baya. Sai kuma ya tabbatar da cewa, Allah mai tausasawa ne ga bayinsa, mai kai su ne matsayin da ba su yi tsammanin kaiwa gare shi ba, domin cikakken iliminsa da hikimarsa cikin al’amura.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, bayan ni’imar da ya cika wa Annabi Yusufu ta ba shi mulki da sanar da shi fassarar mafarki, sai ya koma ga Allah yana mai sake godiya gare shi tare da roƙon sa ya tabbatar da dugadugansa a kan Musulunci har lokacin mutuwarsa, ya kuma haɗa shi da annabawa salihai daga cikin iyayensa da wasunsu a cikin Aljannar Firdausi.

Wannan shi ne ƙarshen labarin Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ‘yan’uwansa wanda Allah ya sanar da Annabinsa Muhammadu (ﷺ); labari ne mai ƙayatarwa wanda yake cike da gargaɗi da darussa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da annabawansa wasu abubuwa na gaibinsa domin su zamo dalili mai tabbatar da annabcinsu.

2. Zukatan mutane ba a hannun mai wa'azi suke ba ballantana ya tursasa su har su yi imani da gaskiyar da yake kiran su a kanta. Zukata duka suna hannun Allah ne shi ne yake sarrafa su yadda ya ga dama.

3. Masu karɓar shiriya su yi imani kaɗan ne a cikin mutane.

4. Suka ga marasa ɗaukar izina da darasi daga ayoyin Allah na halittunsa a sammai da ƙasa.

5. Da yawa masu imani sukan haɗa imaninsu da shirka ko da sani ko cikin rashin sani. Don haka sanin nau'o'in shirka a cikin wannan al'umma abu ne mai matuƙar muhimmanci ga Musulmi don guje wa aukawa cikinsu.

Suratu Yusuf (102-107)

ذَٰلِكَ مِنۡ أَنۢبَآءِ ٱلۡغَيۡبِ نُوحِيهِ إِلَيۡكَۖ وَمَا كُنتَ لَدَيۡهِمۡ إِذۡ أَجۡمَعُوٓاْ أَمۡرَهُمۡ وَهُمۡ يَمۡكُرُونَ ١٠٢ وَمَآ أَكۡثَرُ ٱلنَّاسِ وَلَوۡ حَرَصۡتَ بِمُؤۡمِنِينَ ١٠٣ وَمَا تَسۡـَٔلُهُمۡ عَلَيۡهِ مِنۡ أَجۡرٍۚ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ لِّلۡعَٰلَمِينَ ١٠٤ وَكَأَيِّن مِّنۡ ءَايَةٖ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ يَمُرُّونَ عَلَيۡهَا وَهُمۡ عَنۡهَا مُعۡرِضُونَ ١٠٥ وَمَا يُؤۡمِنُ أَكۡثَرُهُم بِٱللَّهِ إِلَّا وَهُم مُّشۡرِكُونَ ١٠٦ أَفَأَمِنُوٓاْ أَن تَأۡتِيَهُمۡ غَٰشِيَةٞ مِّنۡ عَذَابِ ٱللَّهِ أَوۡ تَأۡتِيَهُمُ ٱلسَّاعَةُ بَغۡتَةٗ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ١٠٧

102. Wannan yana daga labaran gaibu da Muke yi maka wahayinsa; ba ka kuma tare da su lokacin da suka haɗa al'amarinsu suna ƙulle-ƙullen makirci.

103. Yawancin mutane ba za su yi imani ba, komai kwaɗayinka (ga hakan).

104. Kuma ba ka tambayar su lada a kansa (wato Alƙur'ani). Shi ba wani abu ne daban ba in ban da gargaɗi ga talikai.

105. Kuma ayoyi nawa ne a sammai da ƙasa waɗanda (kafirai) suke wucewa ta wajensu, amma suna bijire musu?

106. Yawancinsu kuma ba sa yin imani da Allah sai (an same su) suna masu shirka (da Shi).

107. Yanzu sun amince ne wata azabar Allah mai lullubewa ta zo musu, ko kuwa alƙiyama ta zo musu ba zato ba tsammani, alhalin su ba su sani ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙarin bayani ne a kan ƙissar Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ta gabata. Ya bayyana cewa, duk abin da aka saurara cikin wannan labari tun daga farkonsa har zuwa ƙarshensa gaibi ne na Allah, ba don ya yi wa Annabi (ﷺ) wahayinsa ba, to da bai san komai a kansa ba, domin kuwa ba ya tare da 'yan'uwan Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da suka shirya masa makirci har suka jefa shi cikin kururrumar rijiya daga ƙarshe sauran abubuwan da suka biyo baya suka faru. To wannan shi ne cikakken dalili a kan gaskiyar annabcin Annabi Muhammad (ﷺ).

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Annabi (ﷺ) cewa yawancin mutane fa ba za su yi imani ba duk kuwa da irin bayyanannun hujjoji da ya zo musu da su, don haka kada ya yawaita damuwa a kansu.
Allah kuma ya tabbatar da cewa, Annabi (ﷺ) ba ya karɓar komai daga hannun mutane don ya yi musu waʾazi ballantana su ce abin duniya yake nema, Alƙurʾani da yake karanta musu kuma ba komai ne ba face waʾazi da tunatarwa ga talikai gaba ɗaya, domin su riƙi abin da zai amfane su su kuma guji abin da zai cutar da su.
Sannan Allah ya bayyana yadda yawancin mutane suke gafala da ayoyin Allah da ya ajiye a cikin manya-manyan halittu da ya yi na sammai da ƙasa, kamar rana da wata da taurari da duwarwatsu da tekuna da ƙoramu da bishiyoyi da dabbobi na ruwa da na tudu, amma mutane suna ganin su ba sa ɗaukar wata izina daga gare su su fahimci Kaɗaitar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai.
Ya kuma bayyana cewa, ko da an samu wani ɓangare na imani tare da wasu, sun ba da gaskiya da cewa, shi ne mahalicci mai arzutawa, mai kashewa ya raya, duk da haka suna bauta wa wasu gumaka tare da Allah ko kuma suna daʾawar yana da ɗa. Tsarki ya tabbata gare shi.

Ya tabbata a cikin hadisi daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Mushirikai sun kasance suna cewa: "Mun amsa kiranka (Allah) ba ka da wani abokin tarayya." Sai Annabi (ﷺ) ya ce musu: "Kaiconku, ya isa haka, ya isa haka!" To amma sai su ƙara da cewa: "Sai dai wani abokin tarayyar da shi naka ne, kai ne ke mallakar sa da abin da ya mallaka." Suna faɗar haka ne yayin da suke ɗawafi a Kaʾaba." [Muslim #1185]

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara gargaɗin masu bijire wa ayoyinsa suna haɗa shi da wasu wajen bauta cewa, yanzu su sun amince da cewa wata azaba a nan duniya ta zo musu ta lulluɓe su ta koʾina su rasa mafita daga gare ta? Ko kuma sun yarda alƙiyama ta zo musu ba zato ba tsammani, alhalin ba su san da zuwanta ba ballantana su yi mata wani tanadi? Wannan shi ne ya hana su yin imani da Kaɗaitakar Allah da gaskiyar Manzonsa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne kira zuwa ga Allah ya kasance a kan sunnar Annabi (ﷺ).

2. Wajibi ne mai daʾawa ya zamanto yana kira ne zuwa ga Allah ba zuwa ga kansa ko ƙungiyarsa ko jamaʾarsa ba.

3. Wajibi ne kiransa ya kasance a bisa ilimi da hujja daga Allah da Manzonsa (ﷺ).

4. Duk wani mabiyin Annabi (ﷺ) to lalle ya zamanto mai kira zuwa ga hanyar Annabi (ﷺ) da hujja bayyananniya.

5. Dole ne mai kira zuwa ga Allah ya fara inganta aƙidarsa, ya guji shirka da Allah.

6. Allah yana aiko manzanninsa ne daga cikin mutane kuma maza ne ba mata ba, kuma 'yan birni ne ba 'yan ƙauye ba.

7. Duk labaran da suka zo a Alƙurʾani ƙunshe suke da ɗimbin hikimomi da waʾazuzzuka, ba kawai labarai ne na nishaɗantarwa ba.

8. Alƙur'ani kundin shiriya ne da ya ƙunshi duk abin da ɗan'adam yake buƙata na kyautata rayuwarsa ta duniya da ta lahira.

9. Babu masu shiryuwa da karantarwar Alƙur'ani sai muminai.

Suratu Yusuf (108-111)

قُلْ هَٰذِهِۦ سَبِيلِىٓ أَدْعُوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ ۚ عَلَىٰ بَصِيرَةٍ أَنَا۠ وَمَنِ ٱتَّبَعَنِى ۖ وَسُبْحَٰنَ ٱللَّهِ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿١٠٨﴾ وَمَآ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ إِلَّا رِجَالًا نُّوحِىٓ
إِلَيْهِم مِّنْ أَهْلِ ٱلْقُرَىٰٓ ۗ أَفَلَمْ يَسِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۗ وَلَدَارُ ٱلْءَاخِرَةِ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ ۗ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿١٠٩﴾
حَتَّىٰٓ إِذَا ٱسْتَيْـَٔسَ ٱلرُّسُلُ وَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُمْ قَدْ كُذِبُوا۟ جَآءَهُمْ نَصْرُنَا فَنُجِّىَ مَن نَّشَآءُ ۖ وَلَا يُرَدُّ بَأْسُنَا عَنِ ٱلْقَوْمِ ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿١١٠﴾ لَقَدْ كَانَ فِى قَصَصِهِمْ
عِبْرَةٌ لِّأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ ۗ مَا كَانَ حَدِيثًا يُفْتَرَىٰ وَلَٰكِن تَصْدِيقَ ٱلَّذِى بَيْنَ يَدَيْهِ وَتَفْصِيلَ كُلِّ شَىْءٍ وَهُدًى وَرَحْمَةً لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿١١١﴾

108. Ka ce: "Wannan ce hanyata, ina yin kira zuwa ga Allah, bisa hujja, ni da wanda ya bi ni. Tsarki kuma ya tabbata ga Allah, ni kuwa ba na cikin masu shirka."

109. Ba Mu kuma aiko (manzanni) a gabaninka ba sai maza 'yan birni waɗanda Muke yi wa wahayi. Me ya sa (kafirai) ba za su yi tafiya ba a bayan ƙasa don su ga yadda ƙarshen waɗanda suka rigaye su ya kasance? Lalle kuwa gidan lahira shi ya fi ga waɗanda suke kiyaye dokokin (Allah). Shin ba za ku hankalta ba?

110. Har yayin da manzanni suka ɗebe ƙauna (da imanin mutanensu), su kuma (kafiran) suka yi zaton an faɗa musu ƙarya ne (game da zuwan azabar Allah) sai taimakonmu ya zo musu, sai Muka tserar da wanda Muka ga dama; ba kuwa za a kawar da azabarmu daga mutane masu laifi ba.

111. Haƙiƙa akwai izina a cikin labaransu (annabawa) ga ma'abota hankali. (Alƙur'ani) bai zamanto zance ne da ake ƙirƙirar sa ba, sai dai zance ne da yake gaskata abin da ya rigaye shi (na littattafai), da kuma bayanin komai; shiriya ne kuma da rahama ga mutanen da suke yin imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Manzonsa (ﷺ) ya faɗa wa mutane cewa, wannan tafarkin da yake a kansa shi ne hanyarsa da yake kiran mutane zuwa gare ta a bisa doron hujja bayyananna. Hakanan waɗanda suka bi shi suka karɓi kiransa su ma a kan wannan hanyar tasa suke, suna kuma kira da hujja bayyananna. Sannan ya tabbatar musu cewa, shi ba ya daga cikin masu shirka da Allah, yana cikin masu kaɗaita Allah ne da bauta, tsarki ya tabbata a gare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi ishara da cewa, gabanin Manzon Allah (ﷺ) Annabi Muhammadu bai aiko da wani manzo ba sai daga cikin mazaje ba mata ba, kuma mutum ba aljan ba ba kuma mala'ika ba, ya zama kuma daga cikin mazauna birni ba ɗan ƙauye ba. Saboda haka Ƙuraishawa su bar yin mamakin aiko musu da wani mutum daga cikinsu har ma suna ganin bai fi su da komai ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan al'ummun da ya aika musu da manzanni suka ƙaryata su kuma ya halaka su a dalilin haka, don haka me zai hana waɗannan masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) su yi yawo a bayan ƙasa su ga yadda ƙarshen masu ƙaryata manzannin Allah ya kasance domin su wa'azantu da su? Sai kuma ya ja hankalinsu a kan cewa, ya kamata su fahimci cewa ni'imar gidan lahira ga waɗanda suka kiyaye dokokin Allah a duniya ta fi musu alheri, me ya sa ba sa hankalta su gane abin da ake nuna musu, su bi Allah da Manzonsa su guji saɓa musu?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, manzannin da ya aiko aka ƙaryata su yakan jinkirta azabtar da maƙiyansu na wani ɗan lokaci, har manzannin sukan ɗebe ƙaunar samun nasara a kan maƙiyansu sannan azabar Allah gare su ta yi jinkirin zuwa, har ta kai kafirai suna cewa manzannin nan sun yi musu ƙaryar cewa azabar Allah za ta auko musu idan ba su ba da gaskiya da su ba. To ga shi ba su yi

imanin ba kuma har yanzu azabar ba ta zo ba. Ana cikin haka sai nasarar Allah ta zo wa manzanninsa, azabarsa ta sauka ga kafirai, Allah ya tserar da manzannin da mabiyansu, ya halakar da kafirai. To Ƙuraishawa da duk masu ƙaryata Manzo su sani cewa, idan azabar Allah ta zo babu mai iya kawar da ita.
Sai kuma daga ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimar bayar da labaran manzanni da al'ummunsu, kamar labarin Annabi Yusufu da ‘yanʾuwansa, cewa ba shakka akwai waʾazi ga mutane masu hankali da lura game da su. Don haka Alƙurʾani wanda ya zo da waɗannan labaran ba za ta yiwu a ce zance ne na ƙarya ba, sai dai shi zance ne da yake gaskata duk littattafan Allah da suka gabace shi, kuma cike yake da bayani filla-filla na hukunce-hukuncen shariʾa da duk abin da mutane suke buƙatar sa a rayuwarsu ta duniya da ta lahira, kuma shiriya ce da rahama ga mutanen da suka yi imani, domin su ne kaɗai za su amfana da abin da ya ƙunsa na shiriya da waʾazi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙurʾani littafin Allah ne da ya saukar da shi bisa gaskiya da ya ƙunshi dukkan buƙatar ɗanʾadam ta rayuwar duniya da lahira.

2. Jan hankali zuwa ga tunani cikin halittar sammai, domin su kaɗai sun isa su tabbatar wa da mai hankali Kaɗaitakar Allah Taʾala.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya daidaita a kan Alʾarshinsa, amma daidaito wanda ya dace da shi ba tare da kwatance ko canza maʾana ba.

4. Wajabcin tunani da laʾakari da halittun sama da ƙasa kamar rana da wata da taurari domin ƙarin tabbatar da cancantar Allah a bauta masa shi kaɗai.

5. Fitar da manya-manyan bishiyoyi daga cikin ƙwayoyin iri ƙanana yana mayar wa da mushirikai martani a kan musunta tashi bayan mutuwa, domin sake dawo da ƙasusuwan da suka rududduguе su haɗe su zama jiki mai rai ya fi sauki a kan fitar da babbar bishiya daga ƙwayar iri ‘yar ƙarama.



13-Suratur Ra’ad

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna *‘Suratu ar-Ra’ad’*, kamar yadda yake a cikin *masahif* da littattafan tafsirai, da littattafan hadisai. Kuma wannan shi ne sunanta a wurin malamai magabata
Kalmar *Ar-Ra'adu* da Larabci tana nufin “Tsawa” . Kalmar ta zo ne cikin wannan Sura a aya ta 13, don haka aka ba ta wannan sunan.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun yi saɓani a kan cewa shin wannan Sura *Makkiyya* ce ko *Madaniyya*? Da yawa daga cikin almajiran Abdullahi ɗan Abbas, kamar su Mujahid da Sa’id ɗan Jubairu da Aliyyu ɗan Ɗalha sun ruwaito daga wajensa yana cewa Sura ce *Makkiyya*. Watau an saukar da ita kafin Hijrar Annabi (ﷺ) zuwa Madina. Wannan kuma shi ne ra’ayin Ƙatadatu da wasu daga cikin malamai.
Wasu kuma suna cewa, Sura ce *Madaniyya*. Wannan shi ne faɗin Abdul Malik ɗan Abdul Aziz ɗan Juraiju da Ikrima da Hasanul Basri. Sannan kuma wata ruwaya ce daga Ibn Abbas.
Wasu kuma suka ce Sura ce *Madaniyya* in ban da aya ta (31) ita ce kawai aya *Makkiyya*.
Amma dai magana mafi ƙarfi ita ce, Sura ce *Makkiyya*. Sannan babban jigon da take magana a kansa yana ƙara tabbatar da cewa a Makka aka saukar da ita, domin jigo ne da ya yi ta maimaituwa a cikin surorin da aka saukar kafin hijirar Annabi (ﷺ) zuwa Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ba a ambaci ko ita ta nawa ce ba a lissafin saukar surori.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta arba’in da uku ne (43) a wajen mutanen Kufa. Amma a wajen mutanen Makka da Madina arba'in da huɗu ne (44).

5. Babban Jigonta:
Tabbatar da Kaɗaitakar Allah da kuma tsawatar wa mushirikai a kan kafircinsu da izgli da daddini da suke yi.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Gaskiyar abin da Annabi (ﷺ) yake faɗa na cewa ana yi masa wahayi. Ta fara da girmama lamarin Alƙur’ani da tabbatar da cewa daga Allah yake.
• Tabbatar da ranar alƙiyama da dalilai masu ƙarfi da kuma mayar da martani a kan masu ƙaryata Annabi (ﷺ) masu kuma ƙaryata ranar alƙiyama.
• Tabbatar da narko da azaba ga masu ƙaryata annabawa da wahayin da aka saukar musu.
• Tunatarwa game da ni’imomin Allah ga mutane da tabbatar da cewa shi ne kaɗai ya cancanci a bauta wa. Da tabbatar da cewa, gumaka ba su mallaki wata ni’ima ba kuma ba su san komai ba.

• A Ƙarshe Surar ta yi bayani a kan ƙaddara da kuma shafe abin da Allah ya ga damar shafewa daga cikin abubuwa da ya ƙaddara saboda wata hikima da take cikin hakan.

Suratur Ra'ad (1-4)

الٓمٓرٰۚ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِۗ وَٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَ ٱلۡحَقُّ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يُؤۡمِنُونَ ١ ٱللَّهُ ٱلَّذِي رَفَعَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ بِغَيۡرِ عَمَدٖ تَرَوۡنَهَاۖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ كُلّٞ يَجۡرِي لِأَجَلٖ مُّسَمّٗىۚ يُدَبِّرُ ٱلۡأَمۡرَ يُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّكُم بِلِقَآءِ رَبِّكُمۡ تُوقِنُونَ ٢ وَهُوَ ٱلَّذِي مَدَّ ٱلۡأَرۡضَ وَجَعَلَ فِيهَا رَوَٰسِيَ وَأَنۡهَٰرٗاۖ وَمِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ جَعَلَ فِيهَا زَوۡجَيۡنِ ٱثۡنَيۡنِۖ يُغۡشِي ٱلَّيۡلَ ٱلنَّهَارَۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ ٣ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ قِطَعٞ مُّتَجَٰوِرَٰتٞ وَجَنَّٰتٞ مِّنۡ أَعۡنَٰبٖ وَزَرۡعٞ وَنَخِيلٞ صِنۡوَانٞ وَغَيۡرُ صِنۡوَانٖ يُسۡقَىٰ بِمَآءٖ وَٰحِدٖ وَنُفَضِّلُ بَعۡضَهَا عَلَىٰ بَعۡضٖ فِي ٱلۡأُكُلِۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ٤ الٓمٓرٰۚ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِۗ وَٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَ ٱلۡحَقُّ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يُؤۡمِنُونَ ١ ٱللَّهُ ٱلَّذِي رَفَعَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ بِغَيۡرِ عَمَدٖ تَرَوۡنَهَاۖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ كُلّٞ يَجۡرِي لِأَجَلٖ مُّسَمّٗىۚ يُدَبِّرُ ٱلۡأَمۡرَ يُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّكُم بِلِقَآءِ رَبِّكُمۡ تُوقِنُونَ ٢ وَهُوَ ٱلَّذِي مَدَّ ٱلۡأَرۡضَ وَجَعَلَ فِيهَا رَوَٰسِيَ وَأَنۡهَٰرٗاۖ وَمِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ جَعَلَ فِيهَا زَوۡجَيۡنِ ٱثۡنَيۡنِۖ يُغۡشِي ٱلَّيۡلَ ٱلنَّهَارَۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ ٣ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ قِطَعٞ مُّتَجَٰوِرَٰتٞ وَجَنَّٰتٞ مِّنۡ أَعۡنَٰبٖ وَزَرۡعٞ وَنَخِيلٞ صِنۡوَانٞ وَغَيۡرُ صِنۡوَانٖ يُسۡقَىٰ بِمَآءٖ وَٰحِدٖ وَنُفَضِّلُ بَعۡضَهَا عَلَىٰ بَعۡضٖ فِي ٱلۡأُكُلِۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. *ALIF LAM MIM RA*. Waɗannan ayoyi ne na Littafi (wato Alƙur'ani). Wanda kuma aka saukar maka daga Ubangijinka gaskiya ne, sai dai lalle yawancin mutane ba sa yin imani.

2. Allah Wanda Ya ɗaukaka sammai ba tare da wasu ginshiƙai da kuke ganinsu ba; sannan Ya daidaita bisa Al'arshi; Ya kuma hore muku rana da wata; kowannensu yana gudu zuwa wani lokaci ƙayyadadde. Yana shirya al'amari, Yana bayyana ayoyi don ku sakankance da haɗuwarku da Ubangijinku.

3. Shi ne kuma Wanda Ya shimfiɗa ƙasa Ya kuma sanya turaku (na duwatsu) a cikinta da ƙoramu; kuma daga kowaɗanne 'ya'yan itace Ya sanya ma'aura biyu (mace da namiji); dare yana rufe rana. Lalle a game da waɗannan abubuwan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suke tunani.

4. A cikin ƙasa kuma da akwai yankuna masu maƙotaka da juna, da gonakai na inabai da shuke-shuke da dabinai masu tushiya ɗaya da kuma waɗanda suke kowane tushiyarsa daban, ana shayar da su da ruwa ɗaya, Muna kuma fifita wasunsu a kan wasu wajen ɗanɗano. Haƙiƙa a game da wannan da akwai ayoyi ga mutanen da suke da hankali.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori da suka gabace ta. Kamar yadda muka riga muka ambata cewa, malamai sun yi maganganu mabambanta game da manufar waɗannan haruffa, sai dai ana iya cewa, haruffan suna nuni ne zuwa ga mu'ujizar Alƙur'ani, watau duk da kasancewarsa magana ce da ta gudana da waɗannan haruffa waɗanda Larabawa ma da su suke magana, amma kuma sun kasa kawo wani abu kwatankwacin Alƙur'ani, wanda hakan yake tabbatar da cewa, shi maganar Allah ne ba ta wani mutum ba. Don haka ya bayyana cewa, waɗannan ayoyin da wannan Surar ta ƙunsa ayoyin Alƙur'ani ne wanda littafi ne da ya ƙunshi duk abin da ɗan'adam yake buƙatar sanin sa da ya danganci aƙida ko shari'a. Shi ne abin da Allah ya saukar wa Manzonsa wanda yake gaskiya ne babu wani kokwanto a cikinsa, to amma mutane da dama taurin kai da jayayya sun hana su ba da gakiya da shi.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk halittun da suke sama da ƙasa suna nuna cikakken ikonsa ne da cancantar a bauta masa shi kaɗai, kuma shi ne ya halicci sammai; wata a saman wata, ba tare da ginshiƙai da suke riƙe da su waɗanda kuke iya ganinsu da idanunku ba. Sannan cikin cikar ɗaukakarsa ya daidaita a kan Al'arshinsa daidaitar da ta dace da kamalar Zatinsa. Haka kuma ya hore rana da wata domin amfanin halittunsa; rana da wata kowannensu yana gudu a cikin magudanarsa zuwa wani ƙayyadadden lokaci da Allah ne kaɗai ya san shi. Yana kuma gudanar da al'amuran da ya ga dama a cikin sammai da ƙasa babu mai hana shi. Wannan bayani ne na ayoyin Allah da yake yi wa mutane domin su tabbatar cewa, akwai ranar alƙiyama tana nan tafe, su tashi su yi tanadin aiki na ƙwarai don haɗuwa da Ubangijinsu a wannan rana.
Sannan Allah ya ci gaba da bayyana dalilai na gani da ido masu tabbatar da Ɗayantakarsa da cikar Ƙudurarsa. Daga cikin ayoyi da suke nuna haka akwai duwatsu waɗanda suka zama turaku ga ƙasa don su hana ta motsi da mutanen da ke kanta. Kuma ya halicci 'ya'yan itatuwa iri-iri kowannensu ya yi shi aure biyu, kamar yadda ya yi ɗan'adam da dabbobi mace da namiji. Haka kuma yana rufe hasken rana da duhun dare sai ko'ina ya zama duhu ƙirin. Ya bayyana cewa, duk waɗannan ayoyi ne, watau hujjoji ga mutane masu tunani game da ayyukan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) don su fahimce su su ɗauki izina daga gare su sai hakan ya amfane su wajen gane girman Allah da kaɗaitakarsa.
Ya kuma ci gaba da bayyana wasu dalilan na gani da ido masu tabbatar da cikakkiyar Ƙudurarsa, watau yadda ya halicci ƙasa iri daban-daban masu maƙotaka da juna waɗanda ake shuka abubuwa daban-daban a cikinsu kamar kayan marmari da hatsi da itatuwan dabino waɗanda suke da tushe ɗaya da waɗanda suke da tushe daban-daban, kuma ana shayar da su ruwa ɗaya, to amma sai su fito mabambanta a kamanni da ɗanɗano da girma duk kuwa da cewa, an shuka dukansu a ƙasa ɗaya kuma sun sha ruwa ɗaya. Lalle wannan yana nuna cikar Ƙudurar Allah wanda yake aikata abin da ba wani wanda zai iya aikata irinsa. Babu kuwa waɗanda suke fuskantar waɗannan ayoyi na Allah su fahimce su sai mutane masu hankali.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daga cikin dalilan ɓacewar mushirikai shi ne kwatanta Allah mahalicci da wani mahaluƙi, don haka suka ga abin da mahaluƙi ba zai iya yi ba to Allah ma ba zai iya ba.

2. Yalwar rahamar Allah ga bayinsa; ga shi dai suna ƙaryata shi suna saɓa masa dare da rana suna ƙaryata manzanninsa, amma yana ci gaba da kyautata musu da buɗe musu ƙofofin tuba don su samu rahamarsa ta lahira.

3. Halin bawa ba zai sami daidaito ba har sai ya riƙa hango siffofin nan na Allah guda biyu a tare; siffarsa ta mai gafara da siffarsa ta mai yin uƙuba; ya zamanto mai kyakkyawan fata, mai kuma tsoro. Idan bawa ya rasa ɗaya daga cikinsu to ya hallaka.

4. Duk wata al'umma da aka yi a bayan ƙasa Allah ya aiko musu da annabi wanda ya kirawo su zuwa ga addinin gaskiya.

Suratur Ra'ad (5-7)
*وَإِن تَعۡجَبۡ فَعَجَبٞ قَوۡلُهُمۡ أَءِذَا كُنَّا تُرَٰبًا أَءِنَّا لَفِي خَلۡقٖ جَدِيدٍۗ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ ٱلۡأَغۡلَٰلُ فِيٓ أَعۡنَاقِهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٥ وَيَسۡتَعۡجِلُونَكَ بِٱلسَّيِّئَةِ قَبۡلَ ٱلۡحَسَنَةِ وَقَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِمُ ٱلۡمَثُلَٰتُۗ وَإِنَّ رَبَّكَ لَذُو مَغۡفِرَةٖ لِّلنَّاسِ عَلَىٰ ظُلۡمِهِمۡۖ وَإِنَّ رَبَّكَ لَشَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٦ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ ءَايَةٞ مِّن رَّبِّهِۦٓۗ إِنَّمَآ أَنتَ مُنذِرٞۖ وَلِكُلِّ قَوۡمٍ هَادٍ ٧

5. Idan kuwa kana mamakin (ƙaryata ka da suke yi), to ai abin mamaki shi ne faɗarsu (cewa): "Yanzu idan muka zama turɓaya anya kuwa za a sake halittarmu?" Waɗannan su ne waɗanda suka kafirce wa Ubangijinsu, waɗannan kuma akwai ƙuƙumi (da za a sa musu) a wuyoyinsu. Waɗannan kuwa su ne 'yan wuta madawwama a cikinta.

6. Suna kuma nemanka da gaggauto musu da azaba tun kafin (su nemi) kyakkyawa (wato rahamar Allah), alhali kuwa haƙiƙa misalai (na waɗanda aka halakar) a gabansu sun wuce. Lalle kuma Ubangijinka Ma'abocin gafara ne ga mutane a kan laifuffukansu, kuma lalle Ubangijinka tabbas Mai tsananin azaba ne.

7. Waɗanda suka kafirta suna cewa: "Me ya hana a saukar masa da wata aya daga Ubangijinsa?" Lalle kai mai gargaɗi ne kawai; kowaɗanne mutane kuwa suna da mai shiryawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, idan akwai wani abin mamaki game da maganganun kafirai babu kamar ƙaryata ranar alƙiyama da suke yi, har suna tababa da cewa, yanzu ashe idan sun mutu sun zama ƙasa Allah zai iya sabunta halittarsu? Allah ya bayyana cewa, waɗannan masu wannan maganar su ne suka ƙaryata dawo da rai bayan mutuwa suka kafirce wa Allah Ubangijinsu domin sun nuna kasawar Ƙudurarsa ta tashin matacce bayan mutuwa. Don haka mummunan sakamakon da za su haɗu da shi ranar alƙiyama shi ne, za a sanya musu sarƙoƙin wuta a wuyansu, za kuma su zama ma'abotan wutar Jahannama masu zama a cikinta har abada ba za su mutu ba kuma azaba ba za ta yanke musu ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci yadda waɗannan kafirai suke ƙaryata Annabi (ﷺ) game da kashedin da yake yi musu na azabar da za ta iya auka musu tun a nan duniya sakamakon kafircinsu, don isgili har suna neman sa da ya gaggauto musu da ita maimakon su roƙi rahamar Allah. Wannan yana nuna kafewarsu a kan kafircinsu da rashin yarda da gargaɗi da tsoratarwa da ake yi musu, alhali suna da labaran irin dangogin azaba da Allah ya saukar wa al'ummun da suka gabace su waɗanda suka yi ayyukan kafirci irin nasu, to amma ba sa ɗaukan wani wa'azi ko izina daga gare su. Amma Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi cewa, lalle yana yin gafara ga mutane duk kuwa da laifuffukan da suke tafkawa, ya saurara musu don su tuba ya kuma karɓi tubansu, amma idan har suka doge a kan kafircinsu da miyagun halayensu to su sani cewa, shi fa mai tsananin azaba ne ga masu taurin kai su ƙi tuba, kuma yana iya gaggauto musu wani ɓangare na azabarsa tun a nan duniya kafin ta lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai suka riƙa ƙaryata annabcin Manzon Allah (ﷺ) kamar yadda suka ƙaryata zuwan ranar alƙiyama. Suka riƙa ƙalubalantar sa da ya nuna musu mu'ujiza irin ta annabawan da suka gabace shi kamar Annabi Musa da sandarsa ko Annabi Isa da yake raya matattu, to shi ma me ya sa ba a saukar masa tasa mu'ujizar ba wadda za su gani su yi imani da shi? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya ba su amsa da cewa, shi fa ba wani ba ne sai mai gargaɗi mai tsoratar da mutane azabar Allah, watau shi ba shi da wata mu'ujiza sai wadda Allah ya ba shi, kuma shi aiko shi aka yi zuwa ga mutane ya nuna musu gaskiya domin su bi ta, kuma kowace al'umma da aka taɓa yi a baya suna da annabinsu da Allah ya aiko shi gare su don ya nuna musu hanyar shiriya. Don haka wanda ya shiryu cikinsu don kansa, wanda kuma ya zaɓi ɓata kansa ya cutar ba wani ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yalwar ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Babu wanda ya san abin da yake cikin mahaifar mace sani na haƙiƙa sai Allah shi kaɗai. Ko da kimiyya ta zamani za ta gano nau'in halittar abin da yake cikin cikin mace da yanayin lafiyarsa, to sanin ba zai wuce nan ba, wannan kuma bai kai komai ba na sanin haƙiƙaninsa.

3. Kowane ɗan'adam yana da mala'iku masu tsaron sa dare da rana, suna ba shi kariya daga abin da zai cutar da shi, kamar yadda a cikinsu akwai masu rubuta ayyukansa da maganganunsa.

4. Idan mutane suna so su sami kyakkyawan canji a rayuwarsu, to dole ne sai sun canja halayensu marasa kyau zuwa masu kyau, su bar kafirci su yi imani, su bar saɓon Allah su koma ga ɗa'ar Allah, su bar zalunci su riƙi adalci, to a nan ne za su ga kyakkyawan canji ya samu.

5. Allah yana iya saukar da masifa ga wata al'umma idan wasu daga cikin 'ya'yanta suna laifi ba a hana su ba.

Suratur Ra'ad (8-11)

ٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا تَحۡمِلُ كُلُّ أُنثَىٰ وَمَا تَغِيضُ ٱلۡأَرۡحَامُ وَمَا تَزۡدَادُۖ وَكُلُّ شَيۡءٍ عِندَهُۥ بِمِقۡدَارٍ ۝٨ عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ٱلۡكَبِيرُ ٱلۡمُتَعَالِ ۝٩ سَوَآءٞ مِّنكُم مَّنۡ أَسَرَّ ٱلۡقَوۡلَ وَمَن جَهَرَ بِهِۦ وَمَنۡ هُوَ مُسۡتَخۡفِۭ بِٱلَّيۡلِ وَسَارِبُۢ بِٱلنَّهَارِ ۝١٠ لَهُۥ مُعَقِّبَٰتٞ مِّنۢ بَيۡنِ يَدَيۡهِ وَمِنۡ خَلۡفِهِۦ يَحۡفَظُونَهُۥ مِنۡ أَمۡرِ ٱللَّهِۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُغَيِّرُ مَا بِقَوۡمٍ حَتَّىٰ يُغَيِّرُواْ مَا بِأَنفُسِهِمۡۗ وَإِذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِقَوۡمٖ سُوٓءٗا فَلَا مَرَدَّ لَهُۥۚ وَمَا لَهُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَالٖ ۝١١

8. Allah Yana sane da abin da (mahaifar) kowace mace take ɗauke da shi da kuma abin da mahaifa take ragewa da wanda take ƙarawa; kowane abu kuma a wurinsa yana da gwargwado.

9. (Shi) Masanin abin da ke ɓoye da na sarari ne, Mai girma, Mai cikar ɗaukaka.

10. Duka ɗaya ne (a wurin Allah) wanda ya ɓoye magana daga cikinku da wanda ya bayyana ta da wanda yake ɓuya da daddare da mai bayyana da rana.

11. (Kowanensu) yana da (mala'iku) masu take masa baya a gabansa da kuma bayansa suna kiyaye shi da umarnin Allah. Lalle Allah ba Ya canja abin da mutane suke ciki har sai sun canja halayensu. Idan kuma Allah Ya yi nufin wata azaba ga mutane, to ba mai juyar da ita, ba su kuwa da wani mai jiɓintar su wanda ba Shi ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana cikakkiyar Ƙudurarsa a kan ɗan'adam tun daga halittarsa a cikin mahaifiyarsa har zuwa fitowarsa duniya da rayuwarsa a bayan ƙasa. Allah ya bayyana cewa, yana sane da abin da kowace mace take ɗauke da shi a cikinta, ya san komai game da shi, ya san namiji ne ko mace, mai kyau ko mummuna, mumini ko kafiri, mutumin kirki ko na banza, wanda zai yi tsawon rai ko wanda ba zai yi ba, mai ilimi ko jahili. Yana sane da abin da yake ƙaruwa a mahaifa da abin da yake raguwa na lokacin haihuwarta, ko dai ta haihu kafin cikar wata tara ko ta haihu bayan cikar muddar cikinta, ko ɗan ya zo cikakke da ƙoshin lafiya ko kuma ya zo da wata nakasa ko rashin lafiya, komai a wurin Allah yana da gwargwadon yadda ya tsara shi ba zai ƙaru ba a kan haka ba kuma zai ragu ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah yana haɗa halittar ɗayanku a cikin mahaifiyarsa kwana arba'in yana ɗigon maniyyi; sannan ya zama gudan jini kwatankwacin haka; sannan ya zama tsoka kwatankwacin haka, sannan a aiko masa da mala'ika ya busa masa rai, a kuma umarce shi da abubuwa huɗu, da rubuta arzikinsa da ajalinsa da aikinsa da kuma shi ɗan wuta ne ko ɗan Aljanna." [Bukhari #3208 da Muslim #6893].

Sannan Allah ya bayyana cewa, shi ne masanin duk wani gaibi wanda babu wanda ya san shi, kuma shi ne masanin duk wani abu na sarari da kowa zai iya gani. Shi ne mai girma a siffofinsa da sunayensa da ayyukansa, shi ne kuma maɗaukaki wanda yake sama da duk wani mahaluƙi da Zatinsa da siffofinsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi masanin komai ne babu abin da yake ɓuya gare shi, domin kuwa duk ɗaya ne a wurinsa babu bambanci tsakanin wanda ya bayyana maganarsa a fili aka ji da wanda ya ɓoye ta a ransa bai furta ba, da wanda ya ɓoye kansa cikin dare da wanda ya fito fili rana tsaka, kuma babu wanda Allah bai san abin da yake aikatawa ko yake faɗa ba mai kyau ko mummuna. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda yake tsaron kowane ɗan'adam ta hanyar sanya masa mala'iku a gabansa da bayansa, na rana daban na yamma daban, suna musanyan aiki a tsakaninsu, suna tsaron sa da umarnin Allah daga duk abin da zai cutar da shi wanda Allah ya umarce su su kare shi daga gare shi. Hakanan suna rubuta ayyukansa da maganganunsa ba sa barin komai.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mala'iku suna karɓa-karɓar aikin sa-ido a kanku, wasu da daddare wasu kuma da rana, suna haɗuwa a lokacin sallar asuba da sallar la'asar, sannan waɗanda suka kwana daga cikinsu sai su koma sama, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su, alhalin ya fi su sanin komai: "A wane hali kuka baro bayina?" Sai su ce: "Mun baro su suna salla, mun kuma same su suna salla." [Bukhari #556 da Muslim #1464].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa bayinsa cewa, ba ya canja wani hali da mutane suke ciki na ni'ima da walwala har sai sun canja halayensu masu kyau sun koma ga marasa kyau. Kamar yadda ba zai canja musu wani mummunan hali da suka shiga ba har sai sun canja munanan halayensu sun riƙi kyawawa.
Sannan ya tabbatar musu da cewa, idan ya nufi bayinsa da wata azaba saboda miyagun halayensu na kafirci da saɓon Allah, to babu wanda ya isa ya kawar musu da wannan azabar, ba kuma su da wanda zai jiɓinci al'amuransu ya samar musu abin da suke so, ya kare su daga abin da suke ƙi wanda ba Allah ba. Don haka su guji aikata abin da zai jawo musu fushin Allah da azabarsa, ko kuma su rasa mai kare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan halittun da muke gani a sama da ma waɗanda ba ma gani masu miƙa wuya ne ga Allah, suna sujjada gare shi tare da tsarkake shi ta hanyar tasbihi da godiya a gare shi.

2. Allah yana aiko da tsawa ne don tsoratar da bayinsa da kuma kwaɗaitar da su ni'imarsa.

3. Rundunonin Allah suna da yawa; domin kuwa yana da ikon yi wa bayinsa azaba da abin da ya ga dama daga cikin halittunsa.

4. Haramcin kiran wanin Allah don neman taimako a wurinsa a kan abin da babu mai ikon yin sa sai Allah.

Suratur Ra'ad (12-15)
هُوَ ٱلَّذِى يُرِيكُمُ ٱلۡبَرۡقَ خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَيُنشِئُ ٱلسَّحَابَ ٱلثِّقَالَ ١٢ وَيُسَبِّحُ ٱلرَّعۡدُ بِحَمۡدِهِۦ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ مِنۡ خِيفَتِهِۦ وَيُرۡسِلُ ٱلصَّوَٰعِقَ فَيُصِيبُ بِهَا مَن يَشَآءُ وَهُمۡ يُجَٰدِلُونَ فِى ٱللَّهِ وَهُوَ شَدِيدُ ٱلۡمِحَالِ ١٣ لَهُۥ دَعۡوَةُ ٱلۡحَقِّۖ وَٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَسۡتَجِيبُونَ لَهُم بِشَىۡءٍ إِلَّا كَبَٰسِطِ كَفَّيۡهِ إِلَى ٱلۡمَآءِ لِيَبۡلُغَ فَاهُ وَمَا هُوَ بِبَٰلِغِهِۦۚ وَمَا دُعَآءُ ٱلۡكَٰفِرِينَ إِلَّا فِى ضَلَٰلٍ ١٤ وَلِلَّهِ يَسۡجُدُ مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ طَوۡعٗا وَكَرۡهٗا وَظِلَٰلُهُم بِٱلۡغُدُوِّ وَٱلۡأٓصَالِ ١٥

12. Shi ne Wanda Yake nuna muku walƙiya don tsoratarwa da kuma kwaɗaitarwa, Yake kuma haɗo hadari mai nauyi (ɗauke da ruwa).

13. Tsawa tana tsarkake (Shi) tare da gode masa, malaʾiku ma (suna tasbihi) saboda tsoron Sa, Yana kuma aiko da tsawawwaki sai Ya sami wanda Ya ga dama da su, kuma su (waɗannan kafirai) ga su suna jayayya game da (shaʾanin) Allah. Shi kuwa Mai tsananin ƙarfi ne.

14. Gare Shi (Shi kaɗai) kira na gaske yake; waɗanda kuwa suke bauta wa wasu ba Shi ba, to ba sa amsa musu da komai illa tamkar wanda ya shimfiɗa tafukansa ga ruwa don ya isa bakinsa, ba kuwa zai isa gare shi ba. Addu'ar kafirai kuma ba a komai take ba illa a cikin ɓata.

15. Waɗanda kuma suke sammai da ƙasa (duka) ga Allah suke sujjada sun so ko sun ƙi, haka kuma inuwoyinsu, safe da maraice.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ƙarin wasu ayyukansa masu nuna cikar Ƙudurarsa da buƙatuwar bayinsa gare shi da cancantar a bauta masa shi kaɗai da rashin cancantar a bauta wa wasu ba shi ba. Ya bayyana cewa, shi ne yake nuna wa mutane walƙiya yayin da hadari ya haɗo don tsoratarwa ga wasu kamar matafiya a hanya ko wanda ya yi shanyar kayansa domin busar da su, ko kuma domin kwaɗaitarwa ga wasu kamar manoma masu jiran ruwa domin amfanin gonakinsu ya yi kyau, yana kuma haɗo da hadari mai nauyi wanda yake ɗauke da ruwa.
Daga cikin cikar Ƙudurarsa tsawa ma tana tsarkake shi da yin tasbihi tare da gode masa. Hakanan su ma malaʾiku koyaushe cikin yi masa tasbihi suke suna cike da tsoronsa da girmama shi. Tare da waccan walƙiya mai ba da tsoro da kwaɗaitarwa, har ila yau, yana aiko da tsawa, watau aradu, ɗauke da wuta, ya jefa ta a kan wanda ya ga dama daga cikin bayinsa ya halaka shi da ita.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Zubairu (Allah ya ƙara masa yarda) ya kasance idan ya ji rugugin tsawa (aradu) sai ya yi shiru ya bar maganar da yake yi ya ce: "Tsarki ya tabbata ga wanda tsawa ke tsarkake shi tare da gode masa, malaʾiku ma suke masa tasbihi tare da tsoron sa." [Bukhari, *Al-adabul Mufrad* #723 da Malik, *Muwaḍḍa* #1822].

Abdullahi ɗan Abbas ya kasance idan ya ji rugugin tsawa yakan ce: "Tsarki ya tabbata ga wanda tsawa (aradu) ta yi masa tasbihi." [Bukhari, *Al-adabul Mufrad* #722].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai suna jayayya a kan kaɗaita shi da bauta, alhalin shi mai tsananin ƙarfi ne ga duk mai saɓa masa.
Sannan ya bayyana cewa, shi ne kaɗai ya cancanci kira na gaskiya, wato kira zuwa ga Tauhidi, kuma shi ne kaɗai mai amsa addu'a na gaskiya, amma duk sauran abubuwan da mushirikai suke bauta wa tare da shi ba za su iya tsinana musu komai ba, domin ko roƙon su da suke yi ba za su iya amsa musu shi ba, hasali ma sun zama kamar mai jin ƙishirwa ne da zai riƙa miƙa hannunsa ga ruwa yana jiran ya taso ya kai bakinsa sannan ya sha, to da zai shekara ɗari a haka ba ranar da wannan ruwan zai taso da kansa ya shiga bakinsa. Don haka abin da yake yi aikin wofi ne marar amfani. To haka bautar duk wani mai bautar wanin Allah take; mai roƙon sa da neman agaji a wurinsa ba zai taɓa samun biyan buƙatarsa ba sai dai ya yi ta shan wahalar banza. Don haka Allah ya tabbatar da cewa, addu'ar kafirai ga gumakansu a banza da wofi take tafiya ba za ta amfane su da komai ba sai tsabar wahala.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wata halitta da ke sammai da wadda take ƙasa tana rusuna wa Allah da sujjada, sun so ko sun ƙi. Mumini shi ne wanda yake miƙa wuyansa ga Allah da zaɓinsa, kafiri kuwa shi ne wanda yake rusuna wa Allah ba da sonsa ba, sai dai don ya zama dole ya bi dokokin Allah na halittarsa, gaɓoɓinsa su gudanar da aikinsu kamar yadda Allah ya nufe su su yi, shi ma kansa ya buƙatu ga duk wani abu da Allah ya sanya rayuwarsa ba za ta yiwu ba sai da shi, kamar ci da sha da barci da makamantansu. Hakanan duk inuwowin halittu na sammai da ƙasa suna sujjada ga Allah safe

da maraice. Wannan kuwa babbar aya ce mai tabbatar da cewa, Allah ne kaɗai ya cancanci a bauta masa; duk wani abin bauta ba shi ba ƙarya ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mushirikan Larabawa sun yi imani da Tauhidin Rububiyya, watau yarda da jingina wa Allah ayyukansa shi kaɗai, amma sun ƙaryata Kaɗaitar Allah da bauta.

2. Yarda da Tauhidin Rububiyya yana lizimta wa mutum yarda da Tauhidin Uluhiyya, watau kaɗaita Allah da bauta.

3. Wanda duk bai yi halitta ba to bai cancanci ya zama abin bauta ba.

4. Duk wanda ya kafirce wa Allah to mai makauniyar basira ne komai irin ilimin da yake tutiya da shi, yana rayuwa a cikin duhu ne komai wayewar da yake ganin yana da ita. Mumini shi ne mai gani tar da basirar da Allah ya ba shi, shi ne mai rayuwa a cikin hasken imaninsa da wahayin da Allah ya saukar wa Annabi (ﷺ).

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalai iri-iri a littafinsa Alƙur'ani domin kusanto da fahimtar ma'anoninsa da bayanansa ga mutane don tabbatar da hujja a kansu.

Suratur Ra'ad (16-17)
قُلۡ مَن رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ قُلِ ٱللَّهُۚ قُلۡ أَفَٱتَّخَذۡتُم مِّن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ لَا يَمۡلِكُونَ لِأَنفُسِهِمۡ نَفۡعٗا وَلَا ضَرّٗاۚ قُلۡ هَلۡ يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُ أَمۡ هَلۡ تَسۡتَوِي ٱلظُّلُمَٰتُ وَٱلنُّورُۗ أَمۡ جَعَلُواْ لِلَّهِ شُرَكَآءَ خَلَقُواْ كَخَلۡقِهِۦ فَتَشَٰبَهَ ٱلۡخَلۡقُ عَلَيۡهِمۡۚ قُلِ ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖ وَهُوَ ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّٰرُ ١٦ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَسَالَتۡ أَوۡدِيَةُۢ بِقَدَرِهَا فَٱحۡتَمَلَ ٱلسَّيۡلُ زَبَدٗا رَّابِيٗاۖ وَمِمَّا يُوقِدُونَ عَلَيۡهِ فِي ٱلنَّارِ ٱبۡتِغَآءَ حِلۡيَةٍ أَوۡ مَتَٰعٖ زَبَدٞ مِّثۡلُهُۥۚ كَذَٰلِكَ يَضۡرِبُ ٱللَّهُ ٱلۡحَقَّ وَٱلۡبَٰطِلَۚ فَأَمَّا ٱلزَّبَدُ فَيَذۡهَبُ جُفَآءٗۖ وَأَمَّا مَا يَنفَعُ ٱلنَّاسَ فَيَمۡكُثُ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ كَذَٰلِكَ يَضۡرِبُ ٱللَّهُ ٱلۡأَمۡثَالَ ١٧

16. Ka ce (da su): "Wane ne Ubangijin sammai da ƙasa?" Ka ce: "Allah ne". Ka ce (da su): "Amma yaya kuka riƙi wasu iyayen giji ba Shi ba su zama majiɓinta (gare ku), ba sa mallakar wani amfani ko cuta ga kansu?" Ka ce: "Shin makaho da mai gani za su yi daidai, ko kuwa shin duhu da haske za su yi daidai? Ko sun sanya wa Allah wasu abokan tarayya ne waɗanda suka yi halitta kamar halittarsa, sai halittar ta yi musu kama da juna?" Ka ce: "Allah ne Mahaliccin komai, kuma Shi ne Makaɗaici, Mai rinjaye."

17. Ya saukar da ruwa daga sama, sai magudanai suka kwarara daidai gwargwadon abin da za su iya ɗauka, sai (shi ruwan) mai kwarara ya ɗauko kumfa a samansa. Akwai kuma wata kumfar kamarta daga abin da kuke narkawa a wuta don samun abin ado ko kuwa (ƙera) abin jin dadî. Kamar haka ne Allah Yake ba da misalin gaskiya da ɓarna. To amma kumfar sai ta tafi ta bi iska; amma kuma abin da zai amfani mutane sai ya zauna a ƙasa. Kamar haka ne Allah Yake ba da misali.

A waɗannan ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Larabawa sun yi imani da cewa, Allah shi ne mahaliccin sammai da ƙasa babu wani gunki daga cikin gumakan da suke bauta wa da ya halicce su, amma duk da haka sun nace a kan bautar gumaka ba Allah ba, saboda haka Allah ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tambaye su, wane ne ya halicci sammai da ƙasa? Ya kuma umarce shi da ya ba su amsar cewa, Allah ne mahaliccinsu mai kuma gudanar da su yadda ya ga dama, babu kuma mai musun haka. To amma kuma yaya aka yi suka rungumi wasu abubuwa waɗanda ba za su iya amfanar kansu da komai ba, ba kuma za su

iya kare kansu daga wata cuta ba ballantana har su yi wa wani haka, suka mayar da su majiɓinta alʾamuransu ba Allah ba?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ƙalubalance su da wasu tambayoyi waɗanda suke nuna tufka da warwara cikin aƙidunsu, inda ya ce, shin yanzu kafiri mai makauniyar basira da mumini mai ganin shiriyar Allah za su yi daidai? Ko kuma kafirci, wanda duhu ne, da imani, wanda shi kuma haske ne, za su yi daidai? Ko kuma suna ganin akwai wasu abokan tarayya da Allah waɗanda su ma suka yi halitta kamar yadda ya yi, don haka sai halittun nasa da nasu suka gauraya su kuma suka kasa tantance na kowa, don haka suka zaɓi su bauta musu tare da shi? Babu shakka amsoshin waɗannan tambayoyi duka a fili suke, saboda dalilan da suka gabata masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah a cikin siffofinsa da ayyukansa. Don haka ya umarci Annabi (ﷺ) ya tabbatar musu cewa, Allah ne mahaliccin komai, babu wanda ya yi tarayya da shi cikin halittarsa kuma shi ne kaɗai abin bauta mai rinjaye a kan kowa da komai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar da wasu misalai guda biyu masu nuna rugujewar ƙarya da gaggawa, da kuma wanzuwar gaskiya da tabbatarta har abada.
Misalin farko shi ne ruwan da ya sauka daga sama, ya kwarara cikin rafuka har suka cika taf suna gudu har suka haifar da wata gagarumar kumfa wadda daga ƙarshe za ta baje ta bi iska. A nan Allah ya kwatanta gaskiya da wannan ruwan wanda shi ne zai ci gaba da zama a ƙasa mutane su amfana da shi wajen shansu da shayar da dabbobinsu da shuke-shukensu. Ya kuma kwatanta ƙarya da wannan kumfar da ta taso saman ruwan, ga ta da fari da ɗaukar hankali, amma ba ta da wani amfani ga kowa, daga ƙarshe ma sai ta gushe a neme ta a rasa.
Misali na biyu kuwa shi ne wajen dahuwar tama ko maʾadanan ƙasa da mutane kan yi, yayin da wata kumfa takan taso wadda ita ma takan gushe da gaggawa da zarar wutar dahuwar ta lafa ko an kashe ta, a ƙarshe sai ruwan waɗannan maʾadanan ko tamar shi ne zai wanzu mutane su amfana da shi wajen ƙere-ƙerensu na kayan ado. To duk waɗannan misalan biyu suna nuna cewa, gaskiya ita ce mai tabbata, mai amfani ga mutane, ƙarya kuwa mai gushewa ce ba za ta amfani kowa ba.
Da waɗannan misalan ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake bayyana misalin gaskiya da ƙarya. Ƙarya kamar sharar ruwa ce da kumfarsa mai yawo a kansa, kuma ta yi kama da dattin da yake fita da tsatsa daga ƙarafan maʾadanai yayin da suka sha wuta. Gaskiya kuwa ita ce kamar tataccen ruwa wanda ake sha, yake fitar da tsirrai da ʻyaʾyan itatuwa da ciyawar dabbobi. Haka kuma ta yi kama da abin da yake wanzuwa na maʾadanai bayan an narka shi da wuta, wanda da shi ne, mutane suke amfani wajen ƙere-ƙerensu. To irin waɗannan misalan ne Allah yake ba wa mutane domin su bambance tsakanin ƙarya da gaskiya.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ashʾari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Misalin abin da Allah ya aiko ni da shi na shiriya da ilimi kamar misalin mamakon ruwa ne da ya sauka a wata ƙasa, wani ɓangare nata ƙasa ce mai kyau ta sha ruwan ta fitar da abincin dabbobi da ingirici mai yawa, wani ɓangarenta kuwa tsandauri ne don haka ta riƙe ruwa, Allah ya amfanar da mutane da ita, suka sha ruwan kanta suka shayar da dabbobinsu suka kuma yi shuke-shuke. Sannan ruwan ya sauka wani ɓangare na ƙasa wadda ƙeƙuwa ce ba ta riƙe ruwa ba kuma ta fitar da abincin dabbobi. To wannan shi ne misalin wanda ya fahimci addinin Allah, abin da Allah ya aiko ni da shi ya amfane shi, ya koya ya koyar. Da kuma misalin mutumin da bai damu da hakan ba, bai kuma karɓi shiriyar da Allah ya aiko ni da ita ba." [Bukhari #79 da Muslim #2282].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar mai ilimi a kan marar ilimi. Watau ilimin sanin abin da Allah ya saukar a littafinsa Alƙurʾani da sunnar Manzonsa (ﷺ).

2. Mai lafiyayyen hankali shi ne mai sauraron gaskiya ya karɓe ta ya kuma yi aiki da ita.

3. Wajabcin cika alƙawari da haramcin karya shi.

4. Wajabcin sada zumunci da haramcin yanke shi.

5. Haƙuri mai kyau a wurin Allah shi ne wanda bawa ya yi domin neman yardar Allah, ba don wata manufa ta duniya ba, kamar nuna jarunta ko dauriya don a yaba masa ko don samun wata ɗaukaka ta duniya, domin irin wannan haƙurin ana samun sa har wurin kafiri ma da mutumin da ba Allah a zuciyarsa.

6. Daga cikin kyawawan halayen mumini akwai saka wa wanda ya munana masa da kyakkyawa, ya ba wa wanda ya yi masa rowa, ya yafe wa wanda ya zalunce shi, ya sadar da zumuncin wanda ya yanke masa zumuncinsa, ya kyautata wa wanda ya munana masa, watau dai ba zai rama mugunta da mugunta ba.

7. Allah yana ɗaga darajar mumini a gidan Aljanna saboda nagartar ‘yan’uwansa, ya kai su matakin gidan Aljanna da ba su kai gare shi ba don ya haɗa su da ‘yan’uwansu waɗanda suka ɗara su a gidan Aljanna.

Suratur Ra’ad (18-25)

لِلَّذِينَ ٱسۡتَجَابُواْ لِرَبِّهِمُ ٱلۡحُسۡنَىٰۚ وَٱلَّذِينَ لَمۡ يَسۡتَجِيبُواْ لَهُۥ لَوۡ أَنَّ لَهُم مَّا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا وَمِثۡلَهُۥ مَعَهُۥ لَٱفۡتَدَوۡاْ بِهِۦٓۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ سُوٓءُ ٱلۡحِسَابِ وَمَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ١٨ أَفَمَن يَعۡلَمُ أَنَّمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَ ٱلۡحَقُّ كَمَنۡ هُوَ أَعۡمَىٰٓۚ إِنَّمَا يَتَذَكَّرُ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ١٩ ٱلَّذِينَ يُوفُونَ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ وَلَا يَنقُضُونَ ٱلۡمِيثَٰقَ ٢٠ وَٱلَّذِينَ يَصِلُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيَخۡشَوۡنَ رَبَّهُمۡ وَيَخَافُونَ سُوٓءَ ٱلۡحِسَابِ ٢١ وَٱلَّذِينَ صَبَرُواْ ٱبۡتِغَآءَ وَجۡهِ رَبِّهِمۡ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنفَقُواْ مِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ سِرّٗا وَعَلَانِيَةٗ وَيَدۡرَءُونَ بِٱلۡحَسَنَةِ ٱلسَّيِّئَةَ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عُقۡبَى ٱلدَّارِ ٢٢ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ يَدۡخُلُونَهَا وَمَن صَلَحَ مِنۡ ءَابَآئِهِمۡ وَأَزۡوَٰجِهِمۡ وَذُرِّيَّٰتِهِمۡۖ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ يَدۡخُلُونَ عَلَيۡهِم مِّن كُلِّ بَابٖ ٢٣ سَلَٰمٌ عَلَيۡكُم بِمَا صَبَرۡتُمۡۚ فَنِعۡمَ عُقۡبَى ٱلدَّارِ ٢٤ وَٱلَّذِينَ يَنقُضُونَ عَهۡدَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مِيثَٰقِهِۦ وَيَقۡطَعُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱللَّعۡنَةُ وَلَهُمۡ سُوٓءُ ٱلدَّارِ ٢٥

18. Waɗanda suka amsa (kiran) Ubangijinsu suna da kyakkyawar (makoma). Waɗanda kuwa ba su amsa ba, da a ce duk abin da ke ƙasa gaba ɗaya tare kuma da wani kwatankwacinsa duka nasu ne, to da lalle sun fanshi kansu da shi (ranar alƙiyama). Waɗannan suna da mummunan hisabi, kuma Jahannama ce makomarsu, kuma tir da wannan shimfiɗa.

19. Yanzu wanda ya san cewa abin da aka saukar maka daga Ubangijinka gaskiya ne (zai zama) kamar wanda yake shi makaho ne? Lalle ma’abota hankali ne kaɗai ke wa’azantuwa.

20. (Su ne) waɗanda suke cika alƙawarin Allah kuma ba sa warware alƙawarin.

21. Waɗanda kuma suke sadar da abin da Allah Ya yi umarni a sadar da shi (na zumunci), suke kuma tsoron Ubangijinsu, kuma suke tsoron mummunan hisabi.

22. Waɗanda kuma suka yi haƙuri don neman yardar Ubangijnsu, suka kuma tsai da salla, kuma suka ciyar daga abin da Muka arzuta su da shi a ɓoye da sarari, suke kuma ingije mummunan aiki da kyakkyawa, waɗannan suna da (kyakkyawar) makoma ta gidan (Aljanna).

23. Gidajen Aljanna na dawwama, za su shiga su da waɗanda suka kyautata (aiki) daga iyayensu da matansu da kuma zuriyarsu; mala’iku kuma za su riƙa shigowa wurinsu ta kowace ƙofa.

24. (Suna ce musu): ‘‘Aminci ya tabbata a gare ku saboda haƙurin da kuka yi. To madalla da gida na ƙarshe (watau Aljanna)’’.

25. Waɗanda kuma suke warware alƙawarin Allah bayan sun ƙulla shi, suke kuma yanke abin da Allah Ya yi umarni a sadar da shi, kuma suke ɓarna a bayan ƙasa, waɗannan laʾana ta tabbata a gare su kuma suna da (sakamakon) mummunan gida (shi ne Jahannama).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kasuwar mutane gida biyu:
Na farko, waɗanda suka amsa kiran Ubangijinsu na kaɗaita shi da bauta da ɗaʾa ga Manzonsa (ﷺ), to waɗannan ya yi musu tanadin sakamako mafi kyau, watau Aljanna.
Na biyu kuwa, su ne mutanen da suka ƙi karɓar kiran Allah na kaɗaita shi da bauta, suka kuma ƙi biyayya ga Manzonsa (ﷺ), to waɗannan suna da sakamakon mummunar azaba. Saboda tsammaninta da sun san za a ba su fansar kawunansu idan sun bayar da duk dukiyoyin da suka mallaka da sun yarda sun bayar don su fanshi kawunansu, to amma Allah ya bayyana musu cewa, da a ce za su mallaki duk dukiyar da take bayan ƙasa, a kuma haɗa da wata kamarta su bayar da ita gaba ɗaya wajen fansar kawunansu daga wannan azabar, to ba za a karɓe ta daga wurinsu ba a ba su fansa. Allah ya tabbatar da cewa, za su gamu da mummunan bincike game da munanan ayyukansu, sannan daga ƙarshe mazauninsu shi ne wutar Jahannama wadda za a yi musu shimfiɗa da ita. Lalle kuwa wannan shimfiɗa ta yi matuƙar muni.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwatanta kashi na farko waɗanda su ne suka yi ilimi mai amfani suka kuma yi aiki da iliminsu suka yarda da abin da Allah ya saukar wa Annabi (ﷺ) gaskiya ce da babu wani kokwanto a cikinta, ya kwatanta su da mutum mai gani tar. Sannan ya kwatanta kashi na biyu, watau waɗanda suka ƙi karɓar kira zuwa ga kaɗaita Allah da bauta, suka ƙi yin imani da Alƙurʾani, ya kwatanta su da mutum makaho wanda ba ya ganin komai da ke gabansa balle ya nufi inda yake da lafiya, ya kauce wa abin da zai cutar da shi. Allah ya tabbatar da cewa, waɗannan nauʾin mutane biyu ba za su taɓa zama daidai ba, amma ba kowa ne yake ɗaukar waʾazi ya fahimci misalan da Allah ke bayarwa ba sai mutane masu lafiyayyen hankali kaɗai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffofi takwas na mutanen da suka karɓi kiran Allah da Manzonsa, waɗanda su ne kamar haka:

1. Su ne masu cika alƙawarin da suka ɗauka tsakaninsu da Allah ko tsakaninsu da mutane, ba sa yarda su warware su.

2. Su ne waɗanda suke sada zumuncin da ke tsakaninsu da Allah na bautar sa shi kaɗai da bin umarninsa da barin haninsa, da kuma zumuncin da ke tsakaninsu da junansu na ‘yanʾuwantaka, ba sa yanke shi.

3. Su ne masu tsoron Ubangijinsu don haka suke aikata abin da ya wajabta musu suke barin abin da ya hana su.

4. Su ne masu tsoron ranar hisabi ranar alƙiyama, domin sun yi imani da cewa, duk wanda aka yi masa hisabi na ƙeƙe da ƙeƙe to ya halaka.

5. Su ne masu haƙuri a kan bin Allah da haƙuri a kan abin da ya same su na ƙaddara marar daɗi, da haƙuri a kan kauce wa saɓon Allah, ba don wani abu ba sai domin neman yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Su ne masu tsayar da salla a lokutanta da sharuɗɗanta yadda ya kamata ba tare da sakaci ba.

7. Su ne masu fitar da haƙƙoƙin da ke cikin dukiyoyinsu su bayar a ɓoye don guje wa riya, ko a sarari don a gani a yi koyi da su.

8. Su ne masu saka mummuna da kyakkyawa, watau ba sa ramuwar gayya ko da an cutar da su, sukan kyautata wa wanda ya munana musu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, sakamakon waɗannan mutane masu irin waɗannan kyawawan siffofin ita ce Aljanna, gidan da za su shige shi su zauna har abada babu mai fitar da su. Yana daga cikin cikar niʾimar da Allah zai yi musu a Aljanna shi ne ya haɗa su wuri ɗaya da ‘yanʾuwansu waɗanda suka cancanci shiga Aljanna da kyawawan ayyukansu. Daga cikinsu akwai iyayensu maza da mata da matansu na aure da ‘yaʾyansu domin ya ɗebe musu duk wata kewa. Baya ga wannan kuma malaʾiku suna kawo musu ziyara suna shigowa ta ƙofofi daban-daban suna gaishe su da sallama, suna faɗa musu cewa, aminci ya tabbata gare su a kan haƙurin da suka yi a duniya. Madalla da wannan gidan na ƙarshe, watau Aljanna.
Bayan Allah ya ambaci siffofin waɗanda suka amsa kiransa da sakamakonsu, sai kuma ya ambaci siffofin waɗanda suka ƙi amsa kiransa suka kafe a kan bautar waninsa. Su kuma siffofinsu guda uku ne:

Na farko, warware alƙawarinsu tsakaninsu da Allah na su bauta masa shi kaɗai ba tare da abokin tarayya ba, sai suke yin shirka da shi.
Na biyu, yanke zumuntar da Allah ya yi umarni a sadar da ita.
Na uku, yaɗa ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar kafirci da saɓon Allah da zaluntar bayin Allah da hana mutane karɓar gaskiya.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗannan da cewa, sun cancanci laʾanar Allah da ta malaʾikunsa da bayinsa muminai, don haka sun yi nisa daga samun rahamar Allah, makomarsu ita ce mummunar azaba ta wutar Jahannama.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Alamomin munafuki uku ne: Idan ya yi magana sai ya yi ƙarya; idan ya yi alƙawari sai ya saɓa; idan kuma aka amince masa to zai ci amana.” [Bukhari #33 da Muslim #59].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah ya halicci halitta, bayan ya gama halittar sai zumunta ta tashi ta ce: “Wannan wurin tsayuwa ne na mai neman tsarinka daga yanke zumunci.” Sai Allah ya ce: “E, haka ne. Shin ba za ki yarda in sadar da wanda ya sadar da ke ba, in kuma yanke duk wanda ya yanke ki?” Zumunta ta ce: “E, na yarda!” Allah ya ce: “To na ba ki wannan.” [Bukhari #4830 da Muslim #2554].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samun arziki da rashinsa duka nufin Allah ne.
2. Yalwar arziki ba ya nufin wani girman matsayi a wurin Allah, don haka Allah zai iya ba wa kafiri yalwar arziki ba don yana son sa ba, zai iya hana mumini ba don ba ya son sa ba. Yakan yi haka ne bisa ga hikimarsa; domin yi wa kafiri talala a duniya, shi kuma muminin da zai ƙuntata arzikinsa ya zamanto ƙarin lada ne da matsayi gare shi a lahira.

3. Shiriya da ɓata duk a hannun Allah suke, yana shiryar da wanda ya cancanci shiriya, ya ɓatar da wanda ya zaɓi ɓata.

4. Ƙarancin hankalin kafirai shi ne ya sa su fifita rayuwar duniya a kan ta lahira.

5. Ba duk abin da yake da amfani a gare ka a nan duniya zai amfane ka a lahira ba.

6. Zikiri nutsuwa yake ƙarawa a zuciyar mai yinsa.

Suratur Ra'ad (26-29)

ٱللَّهُ يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقۡدِرُۚ وَفَرِحُواْ بِٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا فِي ٱلۡأٓخِرَةِ إِلَّا مَتَٰعٞ ٢٦ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ ءَايَةٞ مِّن رَّبِّهِۦۚ قُلۡ إِنَّ ٱللَّهَ يُضِلُّ مَن يَشَآءُ وَيَهۡدِيٓ إِلَيۡهِ مَنۡ أَنَابَ ٢٧ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَتَطۡمَئِنُّ قُلُوبُهُم بِذِكۡرِ ٱللَّهِۗ أَلَا بِذِكۡرِ ٱللَّهِ تَطۡمَئِنُّ ٱلۡقُلُوبُ ٢٨ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ طُوبَىٰ لَهُمۡ وَحُسۡنُ مَـَٔابٖ ٢٩

26. Allah ne Yake shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, Yake kuma ƙuntatawa (ga wanda Ya ga dama. (Kafirai) kuma sun yi farin ciki da rayuwar duniya, rayuwar duniya kuwa ba komai ba ce illa ɗan jin daɗi kaɗan dangane da na lahira.

27. Waɗanda suka kafirta kuma suna cewa: "Me ya hana a saukar masa da aya daga Ubangijinsa?" Ka ce: "Lalle Allah Yana ɓatar da wanda Ya ga dama, Yana kuma shiryar da wanda ya koma gare Shi.

rn28. "(Su ne) waɗanda suka yi imani , zukatansu kuma suna nutsuwa da ambaton Allah. Ku saurara, da ambaton Allah ne zukata suke nutsuwa.

29. "Waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to farin ciki ya tabbata a gare su da kuma kyakkyawar makoma."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, arziki duka yana hannunsa ne, shi ne wanda yake rabon sa yadda ya ga dama, ya yalwata wa wanda ya ga dama cikin bayinsa, ya ƙuntata wa wanda ya ga dama gwargwadon hikimarsa da adalcinsa. Don haka ba wa wani arziki ba ya nufin Allah ya fifita shi ko ya zaɓe shi a kan wanda bai ba wa arzuki ba, hakanan wanda ya ƙuntata masa arzikinsa ba yana nufin ba ya son sa ba ne. To amma su kafirai suna farin cikin sun samu jin daɗin duniya, don haka suka maida hankalinsu a kanta ba sa tunanin lahira ko kaɗan, sun manta da cewa, ita rayuwar duniya idan an kwatanta ta da rayuwar lahira ai ɗan jin daɗi ne ɗan kaɗan mai gajeren lokaci zai zo ya wuce kamar ba a yi ba.

An karɓo daga Al-Mustaurid (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duniya idan an kwatanta ta da lahira ba wani abu ba ce sai kamar ɗayanku ne da zai sa ɗan yatsansa a cikin teku, ya duba ya ga abin da zai fito da shi (na ruwan wannan tekun)." [Muslim #2858].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin abin da kafirai suke ƙalubalantar Manzon Allah (ﷺ) da shi, suna cewa, me ya hana Allah ya saukar masa da wata mu'ujiza wadda za su gani da idanunsu su yarda cewa, da gaske Allah ne ya aiko shi, kuma abin da yake karanta musu na Alƙur'ani gaskiya ne? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya ba su amsa da cewa, Allah shi ne wanda yake ɓatar da wanda ya ga dama da adalcinsa, ya shiryi wanda ya ga damar shiriyarsa da falalarsa, don haka su sani cewa, abin ba a hannunsu yake ba ballantana su danganta shi da saukar wata mu'ujiza daga sama, domin ko da Allah ya saukar da mu'ujizar idan bai ga damar su shiriya ba to ba za su shiryu ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffar waɗanda suke shiryuwa da shiriyarsa da cewa, su ne waɗanda suka yi imani da shi a matsayin Allah Ɗaya abin bauta ba tare da shirka ba, kuma zukatansu suke samun nutsuwa da ambaton Allah da karatun littafinsa Alƙur'ani da sauraronsa. Lalle kuwa da ambaton Allah ne kaɗai zukata kan samu natsuwa da gushewar kewa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ambaton siffofin waɗannan bayi nasa nagari da cewa, su ne waɗanda suka yi imani da Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa da ranar lahira sannan ayyukansu na ƙwarai suka gaskata imaninsu. Allah kuma ya tabbatar musu da samun gwaggwaɓan sakamako a lahira domin za su gamu da farin ciki mai ɗorewa a gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya bayyana cewa, kafiran Ƙuraishawa suna kafirce wa Mai rahama, domin ishara ga yawan haƙurinsa da bayanin mummunar ɗabi'ar kafirai da butulcinsu ga Allah, domin shi yana kyautata musu da rahamarsa a duniya amma su suna kafirce masa da ƙaryata Manzonsa.

2. Asali Allah ya saukar da littattafansa ne domin shiriyar bayinsa, ba domin amfani da su wajen bayyana wani abin mamaki na mu'ujiza ba; wannan wani al'amari ne da Allah yakan zartar da shi lokacin da ya ga dama gwargwadon yadda ya so.

3. Ba a taɓa saukar wa wani annabi mu'ujiza ba da ta kai mu'ujizar Alƙur'ani.

4. Masifu sukan auku a wasu lokuta saboda kafirci da saɓon Allah, don haka ba za su gushe ba sai da imani da tuba zuwa gare shi.

5. Abin da yake kan mai wa'azi shi ne kawai kira zuwa ga Allah da bayanin gaskiya, amma shiriyar mutane ba a hannunsa take ba.

6. Kada wani ya yi mamakin irin izgilin da yake fitowa daga kafirai ko ɓatanci ga Annabi (ﷺ); wannan ɗabi'a ce daɗaɗɗiya ta kafirai tun gabanin aiko da Manzon Allah, har bayan aiko shi ma haka ne zai ci gaba da faruwa har Allah ya naɗe ƙasa da abin da yake kanta.

Suratur Ra'ad (30-32)
كَذَٰلِكَ أَرۡسَلۡنَٰكَ فِيٓ أُمَّةٖ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهَآ أُمَمٞ لِّتَتۡلُوَاْ عَلَيۡهِمُ ٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ وَهُمۡ يَكۡفُرُونَ بِٱلرَّحۡمَٰنِۚ قُلۡ هُوَ رَبِّي لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُ وَإِلَيۡهِ مَتَابِ ٣٠ وَلَوۡ أَنَّ قُرۡءَانٗا سُيِّرَتۡ بِهِ ٱلۡجِبَالُ أَوۡ قُطِّعَتۡ بِهِ ٱلۡأَرۡضُ أَوۡ كُلِّمَ بِهِ ٱلۡمَوۡتَىۗ بَل لِّلَّهِ ٱلۡأَمۡرُ جَمِيعًاۗ أَفَلَمۡ يَاْيۡسِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن لَّوۡ يَشَآءُ ٱللَّهُ لَهَدَى ٱلنَّاسَ جَمِيعٗاۗ وَلَا يَزَالُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ تُصِيبُهُم بِمَا صَنَعُواْ قَارِعَةٌ أَوۡ تَحُلُّ قَرِيبٗا مِّن دَارِهِمۡ حَتَّىٰ يَأۡتِيَ وَعۡدُ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُخۡلِفُ ٱلۡمِيعَادَ ٣١ وَلَقَدِ ٱسۡتُهۡزِئَ بِرُسُلٖ مِّن قَبۡلِكَ فَأَمۡلَيۡتُ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ ثُمَّ أَخَذۡتُهُمۡۖ فَكَيۡفَ كَانَ عِقَابِ ٣٢

30. Kamar haka Muka aiko ka cikin al'umma wadda tuni wasu al'ummun sun wuce kafinta, don ka karanta musu abin da Muka yi maka wahayinsa, alhali kuwa su suna kafirce wa *Arrahamanu*. Ka ce: "Shi ne Ubangijina, babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, gare Shi kawai na dogara, kuma gare Shi kawai tubata take."

31. Da a ce akwai wani abin karantawa da za a gusar da duwatsu da shi, ko kuma a keta ƙasa da shi, ko kuma a yi magana da matattu da shi, (to da wannan Alƙur'anin ne). Bari dai, dukkanin al'amari gaba ɗaya na Allah ne. Shin waɗanda suka yi imani ba su san da cewa da Allah Ya ga dama da Ya shiryi mutane gaba

ɗaya ba? Kafirai kuwa azaba ba za ta daina samun su ba saboda abin da suka aikata, ko kuwa ta faɗo kusa da gidajensu har sai alƙawarin Allah ya zo. Lalle Allah ba Ya saɓa alƙawari.

32. Haƙiƙa an yi wa manzannin da suka gabace ka izgili, sai Na yi wa waɗanda suka kafirta talala, sannan Na damƙe su. To yaya uƙubata ta kasance (a gare su)?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana wa Annabi (ﷺ) cewa, ba shi ne farau ba a cikin manzanni; gabaninsa Allah ya aiko da wasu annabawa da yawa zuwa ga al'ummunsu. Don haka shi ma ya aiko shi ne zuwa ga wannan al'umma domin ya karanta musu Alƙur'ani da aka yi masa wahayinsa wanda ya isa ya zama dalili mai nuna gaskiyarsa, da a ce kafirai za su nutsu su saurare shi su yi tunani a kai, to amma abin takaicin shi ne suna jayayya da musu ne a kan haka, domin ta kai su har suna kafirce wa sunan Allah mai rahama baya ga shirka da shi da suke yi. Kafiran Ƙuraishawa sun kasance suna ƙyamar su siffanta Allah da Mai rahama, domin haka ne a lokacin sulhun Hudaibiyya da Manzon Allah (ﷺ) ya yi umarni da rubuta '*Bismillahir Rahmanir Rahim*' a takardar sulhu suka ƙi amincewa, suka ce su sam ba su san haka ba. [Dubi, Bukhari #2731, 2732].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: Lalle sunayen da Allah ya fi so su ne Abdullahi da Abdurrahman." [Muslim #2132].

Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa wa kafirai cewa, shi mai wannan suna *Arrahmanu* wanda suke kafirce wa, shi ne Ubangijinsa abin bautarsa na gaskiya, wanda kuma da shi ya dogara cikin duk al'amuransa, kuma gare shi yake tuba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da kasancewar Alƙur'ani shi ne mafi girman mu'ujizar Annabi (ﷺ) kuma ba a taɓa samun wata mu'ujiza ta wani annabi da ta kai tasa ba. Allah ya bayyana cewa, da akwai wani littafi daga littattafan da ya saukar wanda duwatsu za su riƙa barin wurarensu saboda shi, ko kuma a tsattsage ƙasa da shi, ta koma gaba ɗayanta ta zama ƙoramu da marmaro na ruwa, ko kuma a karanta shi ga matattu su sake rayuwa, to da kuwa wannan Alƙur'anin ne da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Manzonsa Muhammadu (ﷺ), watau shi ne zai zamanto da irin wannan matsayi a cikin sauran littattafan da Allah ya saukar, domin shi hujja ce bayyananniya mai matuƙar tasiri ga zukata, da a ce su waɗannan kafiran suna da zukata masu tsoron Allah, to amma ina! Sun kasance kawai masu jayayya ne da ƙaryatawa, ba su san cewa, duk wani al'amari na Allah ne ba, daga ciki har da batun saukar da wata mu'ujiza wadda suke nema.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin muminai da cewa, ba su san da cewa idan da Allah ya ga damar ya shiryar da mutane gaba ɗaya, ba tare da saukar da wata mu'ujiza ba, ai da ya aikata haka, domin babu wani abu da zai gagare shi, to amma kuma ba haka ya ga dama ba.
Sannan Allah ya tsoratar da kafirai da irin azabar da za ta same su idan suka ci gaba da ƙaryata gaskiya da jayayya da Annabi (ﷺ), ya tabbartar musu da cewa, ba za su gushe ba wata matsananciyar musiba mai ƙwanƙwasa tana auka musu saboda kafircinsu da yawan saɓon Allah da suke yi, ko kuma wata azaba ta sauko kusa da gidajensu, watau Annabi (ﷺ) da sahabbansa su kai musu farmaki har gida su ci su da yaƙi.
Sannan azabar duniya ta ci gaba da samun su har lokacin da alƙawarin Allah zai zo, shi ne tashin alƙiyama a lokacin da za su gamu da azaba marar yankewa, kuma wannan abu ne tabbatacce domin Allah ba ya saɓa alƙawari.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) da cewa, ya yi haƙuri a kan abin da yake gani na izgili da gallazawa da kafirai suke yi masa; ba a kansa aka fara yin haka ba, kafiran da suka gabata sun yi wa manzanninsu irin wannan izgilin da cin zarafi, kuma Allah ya saurara musu na wani ɗan lokaci har suka fara zaton ko manzanninsu ƙarya suke faɗa musu, kuma ma babu abin da zai same su, sai kawai Allah ya damƙe su mummunar damƙa, ya saukar musu da azabarsa iri-iri wadda idan mutum ya gan ta zai ga irin

tsananinta, to don haka su ma waɗannan kafiran kada su ruɗu da jinkirtawar da ake musu, duk ranar da Allah zai damƙe su ba za su ji da daɗi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya riƙe wani abin bauta ba Allah ba, to ba zai iya tabbatar da cancantar bautarsa da wata hujja ba sai dai magana ta fatar baki wadda babu ƙanshin gaskiya a cikinta ko kaɗan.

2. Idan Shaiɗan ya nufi ɓatar da mutum yakan ƙawata masa ƙarya da saɓon Allah sai ya riƙa ganin su abubuwa ne masu kyau.

3. Shiriya tana hannun Allah ne shi kaɗai.

4. Duk wata azaba da za ta samu kafiri a nan duniya to ba komai ba ce dangane da ta lahira. Shi ya sa duniya take Aljanna ga kafiri.

Suratur Ra'ad (33-34)

أَفَمَنْ هُوَ قَآئِمٌ عَلَىٰ كُلِّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْۗ وَجَعَلُواْ لِلَّهِ شُرَكَآءَ قُلْ سَمُّوهُمْۚ أَمْ تُنَبِّـُٔونَهُۥ بِمَا لَا يَعْلَمُ فِى ٱلْأَرْضِ أَم بِظَٰهِرٍ مِّنَ ٱلْقَوْلِۗ بَلْ زُيِّنَ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ مَكْرُهُمْ وَصُدُّواْ عَنِ ٱلسَّبِيلِۗ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ ﴿٣٣﴾ لَّهُمْ عَذَابٌ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَاۖ وَلَعَذَابُ ٱلْءَاخِرَةِ أَشَقُّۖ وَمَا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن وَاقٍ ﴿٣٤﴾

33. Yanzu wanda Yake tsaye a kan kula da kowane rai game da abin da ya aikata, (zai zama daidai da wanda ba haka ba?) Sun kuma sanya wa Allah abokan tarayya. Ka ce: (da su) "Ku faɗa min sunayensu. Ko kuwa kuna ba Shi labarin abin da bai sani ba ne a bayan ƙasa, ko kuma dai kun riƙe wata ɓatacciyar magana ce?" Bari dai; an dai ƙawata wa kafirai makircinsu ne kawai, aka kuma toshe musu hanyar (Allah). Wanda kuwa Allah Ya ɓatar to ba shi da wani mai shiryarwa.

34. Suna da wata azaba a rayuwar duniya; kuma lalle azabar lahira ita ta fi tsanani; ba su kuwa da wani mai kare su daga (azabar) Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana rashin hankalin kafirai masu barin bautar Allah su kama bautar wasu gumaka marasa amfani, da cewa, yanzu Allah wanda yake tsaye da kula da arzikin duk halittunsa, yake kallon abin da kowane rai yake aikatawa, wanda zai yi masa sakayya a kansa, shi ne ya dace a bauta wa, ko kuwa waɗannan gumakan nasu waɗanda ba su san komai ba, ba kuma sa tsinana musu komai? To amma kafirai saboda rashin tunaninsu sai suka sanya wa Allah kishiyoyi suna bautar su ba Allah ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tambaye su su yi masa bayanin su wane ne waɗannan ababen bautar nasu, idan har suna da gaskiya a kan da'awar da suke yi na allantakarsa; ko kuma suna faɗa wa Allah abin da bai san da shi ba ne a bayan ƙasa na wasu abokan tarayya da shi? Tabbas, Allah shi ne masanin komai na sarari da na ɓoye, da a ce yana da wani abokin tarayya to da ya san da shi ya kuma ba da labarinsa; ko kuma dai suna faɗa wa Allah wata ɓatacciyar magana ce wadda babu gaskiya a cikinta sai zato da shaci-faɗi? Sai a ƙarshe dai Allah ya tabbatar da cewa, kafirai ba su da wata hujja da suke riƙe da ita ta yin watsi da bautar Allah shi kaɗai su kama wasu abubuwan bauta marasa amfani; Shaiɗan ne dai kawai ya ƙawata musu makircinsu sai suka kafirce wa Allah, daga nan ya raba su da hanyar shiriya. Duk kuwa wanda Allah ya ɓatar da shi daga hanyar shiriya to babu wanda zai iya shiryar da shi.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗannan kafirai wanda shi ne azabar duniya ta kisa a fagen yaƙi da faɗawa hannun muminai a matsayin fursunonin yaƙi. Sannan kuma azabar lahira wadda take jiran su ta fi ta duniya tsanani, saboda azaba ce mai bala'in raɗaɗi kuma ba mai yankewa ba. Ga shi kuma ba su da mai kare su daga wannan azabar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ni'imar gidan Aljanna ba ta ƙarewa har abada.

2. Da yawa daga waɗanda suka musulunta cikin ma'abota littafi suna yin farin ciki da abin da ya sauka na Alƙur'ani, domin sun fahimci yana gaskata ilimin littafin da yake hannunsu.

3. Babban aikin da Allah ya ɗora wa kowane manzo shi ne kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai da kauce wa shirka da shi.

4. Haɗarin da ke tattare da bin son zuciya bayan ilimin da ya zo, domin hakan yana jawo azabar Allah.

5. Duk wanda ya ƙi bin wahayin da ya zo daga Allah, to lalle zai bi soye-soyen zukatan wasu mutane ne.

6. Babu yadda fahimtar Alƙur'ani za ta yiwu ba tare da fahimtar harshen Larabci ba.

7. Duk wanda ya saki gaskiya ya kama ƙarya Allah ba zai ƙyale shi ba komai matsayinsa; don haka ne ya fuskantar da gargaɗi ga Annabi (ﷺ) duk kuwa da cewa, ya tsare shi daga aikata laifuka.

Suratur Ra'ad (35-37)

۞مَّثَلُ ٱلۡجَنَّةِ ٱلَّتِي وُعِدَ ٱلۡمُتَّقُونَۖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ أُكُلُهَا دَآئِمٞ وَظِلُّهَاۚ تِلۡكَ عُقۡبَى ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّعُقۡبَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٱلنَّارُ ٣٥ وَٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَفۡرَحُونَ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَۖ وَمِنَ ٱلۡأَحۡزَابِ مَن يُنكِرُ بَعۡضَهُۥۚ قُلۡ إِنَّمَآ أُمِرۡتُ أَنۡ أَعۡبُدَ ٱللَّهَ وَلَآ أُشۡرِكَ بِهِۦٓۚ إِلَيۡهِ أَدۡعُواْ وَإِلَيۡهِ مَابِ ٣٦ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلۡنَٰهُ حُكۡمًا عَرَبِيّٗاۚ وَلَئِنِ ٱتَّبَعۡتَ أَهۡوَآءَهُم بَعۡدَ مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلۡعِلۡمِ مَا لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا وَاقٖ ٣٧

35. Misalin Aljannar nan da aka yi wa masu taƙawa alƙawari da ita; ƙoramu ne suke gudana ta ƙarƙashinta; abincinta kuma mai dawwama ne da kuma inuwarta. Wannan shi ne makomar waɗanda suka kiyaye dokokin Allah; makomar kafirai kuma ita ce wuta.

36. Waɗanda kuwa Muka bai wa littafi (muminansu) suna farin ciki da abin da aka saukar maka; akwai kuma wasu daga ƙungiyoyi waɗanda suke musun wani sashi nasa. Ka ce: "Ni dai an umarce ni ne kawai da in bauta wa Allah, kada kuma in tara wani abu da Shi. Kuma zuwa gare Shi kawai nake kira, wurinsa ne kawai kuma makomata."

37. Kamar haka Muka saukar da shi (Alƙur'ani), ya zama hukunci, da harshen Larabci. Lalle kuma idan ka bi son ransu bayan abin da ya zo maka na ilimi, to ba ka da wani majiɓinci ko mai kariya daga (azabar) Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka kiyaye dokokinsa, suka aikata abin da ya wajabta musu suka bar wanda ya haramta musu, da cewa, suna da gidan Aljanna wadda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashin gidajenta da bishiyoyinta, ga kayan marmarin cikinta ba sa yankewa, hakanan inuwarta ba ta gushewa ba ta kuma raguwa. Amma waɗanda suka kafirce wa Allah kuwa sakamakonsu wutar Jahannama ce za su zauna cikinta ba fita har abada.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Sahabbai sun ce wa Manzon Allah (ﷺ): "Ya Maʾaikin Allah, yaya muka ga ka miƙa hannu daga inda kake tsaye (watau cikin sallar kusufi) ka kamo wani abu, sai kuma muka ga ka dawo da baya?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Tabbas na ga Aljanna ne, sai na kamo wata hantsar kayan marmari daga cikinta, da na ɗauko muku shi da kun yi ta cin sa har ƙarshen rayuwar duniya." [Bukhari #1052 da Muslim #907].

An karɓo daga Sahlu ɗan Saʾad (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle a cikin Aljanna akwai wata bishiya da mahayin abin hawa zai yi tafiyar tsawon shekara ɗari a ƙarƙashin inuwarta bai kai ƙarshenta ba." A ruwayar Abu Saʾid Al-Khudri ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle a cikin Aljanna akwai wata bishiya da mahayin ingarman doki mai gudu zai yi gudu tsawon shekara ɗari a cikin inuwarta bai kai ƙarshenta ba." [Bukhari #6552, 6553 da Muslim #2827].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Yahudawa da Nasara waɗanda Allah ya ba su littattafai, suna farin ciki da Alƙurʾani yayin da suka ji ya yi daidai da abin da ya zo a littattafansu, to amma kuma daga cikinsu akwai waɗanda suke ƙaryata wasu ayoyi na Alƙurʾani waɗanda suka saɓa wa son zuciyarsu, ko kuma ayoyin da suke ɗauke da bayanin canja littattafan Allah da suka yi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya sanar da su cewa, shi Allah ya umarce shi ne kawai da ya bauta masa shi kaɗai ba tare da ya haɗa komai da shi ba, kuma zuwa gare shi kaɗai yake kira kuma makomarsa gare shi kaɗai take, kuma da wannan koyarwar ce Attaura da Linjila suka sauka.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda ya aiko da manzanni gabanin Manzon Allah (ﷺ) ya kuma saukar musu da littattafai daga sama, to hakanan ya saukar wa da Annabi (ﷺ) littafin Alƙurʾani wanda yake bayani ne dalla-dalla babu wata sarƙaƙiya a cikinsa kuma a cikin harshen Larabci mai cike da fasaha da azanci, Allah kuma ya ɗaukaka darajar Annabinsa da wannan Alƙurʾani a kan sauran annabawa, don haka sai ya gargaɗe shi da cewa, idan har ya kuskura ya amince da son zuciya irin ta Yahudu da Nasara masu neman sa da ya shafe abin da ya saɓa wa soye-soyen zukatansu daga Alƙurʾani bayan abin da ya zo masa na ilimin da Allah ya sanar da shi, to ya sani cewa, ba shi da wani majiɓincin alʾamarinsa in ba Allah ba wanda zai taimaka masa a kan abokan gabarsa, haka kuma ba shi da wanda zai kare shi daga azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin cewa, manzannin Allah mutane ne sun yi aure kuma sun haifi 'yaʾya.

2. Bayanin falalar aure da samun zurriyya.

3. Muʾujiza ba a hannun manzanni take ba ballantana su kawo ta duk lokacin da suka ga dama; tana hannun Allah ne shi ne mai kawo ta lokacin da ya ga dama.

4. Babu wani nauyi da ya rataya a wuyan masu kira zuwa ga Allah in ban da isar da saƙon Allah zuwa ga mutane, ikon ciyar da ita gaba yana wurin Allah shi kaɗai, don haka kada gwiwoyinsu su yi sanyi don ganin an sami wani jinkiri ko wani tsaiko wajen samun nasara a aikinsu.

5. Ɗaukar izina daga abubuwan da suke faruwa a duniya na sauye-sauye, watau rushewa bayan ginuwa da mutuwa bayan rayuwa da ƙasƙanci bayan ɗaukaka da tawaya bayan cika. Idan kowa yana iya ganin waɗannan sauye-sauye to me ya sa kafirai ba za su ji tsoron kada Allah ya canja wani halin da suke ciki ba

na ɗaukaka zuwa ƙasaƙanci ko na ƙarfi zuwa rauni ko na masu rinjaye da nasara zuwa ga waɗanda za a rinjaya a yi nasara a kansu?

6. Cin nasara a kan kafirai ya fara ne tun lokacin rayuwar Manzon Allah (ﷺ) ta hanyar kashe manyansu a wurin yaƙe-yaƙe da kama wasu da cinye garuruwansu da yaƙi.

7. Makircin da kafirai suka yi wa Manzon Allah ba shi ne na farko ba, tun tuni kafirai suka yi ta ƙulla wa manzanninsu makirce-makirce, to amma daga ƙarshe Allah ya bayar da nasararsa ga muminai ya karya kadarin kafirai.

8. Allah ya yi umarni da kafa shaida da malaman Ahlul Kitabi domin su ne suke da masaniya a kan al'amarin. Komai kuwa ana neman shaida ne daga waɗanda suka san shi ba waɗanda ba su san komai a kansa ba, shi ya sa ba a kafa shaida da mushirikan Larabawa ba ko kuma sauran al'ummu domin ba su da wani ilimi a kan al'amarin.

Suratur Ra'ad (38-43)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا رُسُلٗا مِّن قَبۡلِكَ وَجَعَلۡنَا لَهُمۡ أَزۡوَٰجٗا وَذُرِّيَّةٗۚ وَمَا كَانَ لِرَسُولٍ أَن يَأۡتِيَ بِـَٔايَةٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ لِكُلِّ أَجَلٖ كِتَابٞ ٣٨ يَمۡحُواْ ٱللَّهُ مَا يَشَآءُ وَيُثۡبِتُۖ وَعِندَهُۥٓ أُمُّ ٱلۡكِتَٰبِ ٣٩ وَإِن مَّا نُرِيَنَّكَ بَعۡضَ ٱلَّذِي نَعِدُهُمۡ أَوۡ نَتَوَفَّيَنَّكَ فَإِنَّمَا عَلَيۡكَ ٱلۡبَلَٰغُ وَعَلَيۡنَا ٱلۡحِسَابُ ٤٠ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّا نَأۡتِي ٱلۡأَرۡضَ نَنقُصُهَا مِنۡ أَطۡرَافِهَاۚ وَٱللَّهُ يَحۡكُمُ لَا مُعَقِّبَ لِحُكۡمِهِۦۚ وَهُوَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ٤١ وَقَدۡ مَكَرَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ فَلِلَّهِ ٱلۡمَكۡرُ جَمِيعٗاۖ يَعۡلَمُ مَا تَكۡسِبُ كُلُّ نَفۡسٖۗ وَسَيَعۡلَمُ ٱلۡكُفَّٰرُ لِمَنۡ عُقۡبَى ٱلدَّارِ ٤٢ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَسۡتَ مُرۡسَلٗاۚ قُلۡ كَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدَۢا بَيۡنِي وَبَيۡنَكُمۡ وَمَنۡ عِندَهُۥ عِلۡمُ ٱلۡكِتَٰبِ ٤٣

38. Haƙiƙa kuma Mun aiko manzanni a gabaninka, Muka kuma ba su matan aure da zurriya. Bai kuma kamata ba ga wani annabi ya zo da wata aya (da za a neme shi da ya kawo ta) sai da izinin Allah. Kuma kowane lokaci yana nan a rubuce.

39. Allah Yana shafe abin da ya ga dama, Yana kuma tabbatar (da abin da ya ga dama); kuma a wurinsa asalin littafi yake.

40. Ko dai Mu nuna maka irin sashin abin da Muke yi musu gargaɗi da aukuwarsa, ko kuma Mu karɓi ranka (kafin lokacin), abin da yake kanka kawai shi ne isar da aike, Mu kuma hisabi yana a kanmu.

41. Yanzu ba sa ganin cewa Muna zaike wa ƙasa Muna ta cinye iyakokinta? Allah ne Mai yin hukunci, babu kuma mai yin gyara ga hukuncinsa. Shi ne kuma Mai saurin yin hisabi.

42. Haƙiƙa kuma waɗanda suke gabaninsu sun ƙulla makirci, (sakamakon) ƙulle-ƙulle dukkaninsa ga Allah yake; Yana sane da abin da kowane rai yake aikatawa. Ba da daɗewa ba kuma kafirai za su san wane ne mai kyakkyawan gidan (ƙarshe).

43. Kafirai kuma suna cewa: "Kai ba manzo ba ne." Ka ce (da su): "Allah Ya isa shaida tsakanina da ku, da kuma wanda yake da ilimin Littafi."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Annabi (ﷺ) ba shi ne farau a cikin manzanni ba wanda ya kasance mutum mai aure ya hayayyafa; an aiko manzanni da yawa gabaninsa kuma sun auri mata har sun samu 'ya'ya da jikoki, wannan bai zama abin suka ga manzancinsu ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da martani ga kafirai masu neman sai Annabi (ﷺ) ya zo musu da wata muʾujiza sannan ne za su yi imani da shi, Allah ya tabbatar musu da cewa, wannan abin da suke nema daga Annabi (ﷺ) ba a hannunsa yake ba, domin kuwa babu wani manzo da zai zo da wata muʾujiza sai da izinin Allah.
Sai kuma ya bayyana musu cewa, komai da suke gani ya wakana, to da ma Allah ya riga ya ƙaddara samuwarsa a wannan lokacin, ba zai rage lokacinsa ba ba kuma zai ƙara ba, don haka su daina ganin abin da Annabi (ﷺ) yake tsoratar da su na azaba bai zo ba, har su yi tsammanin ko ba gaskiya yake faɗa musu ba; lokacinsa ne bai zo ba, idan ya zo to babu mai kawar da shi. Sannan kuma wani abu da ba su sani ba shi ne, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana shafe abin da ya ga dama na alheri ko na sharri, na rabauta ko na taɓewa, ko shariʾa da hukunce-hukunce, yana kuma tabbatar da wanda ya ga dama, domin Lauhul Mahafuzu kacokam yana wurinsa, komai kuma yana nan tattare a cikinsa, duk abin da ya bayyana na shafe wani abu ko tabbatar da shi yana yin daidai ne da abin da yake cikin Lauhul Mahafuzu ba ya saɓawa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Annabi (ﷺ) cewa, aikinsa kawai shi ne isar da saƙo, amma me zai faru ga waɗanda suka bijire wa kiransa kuma mene ne sakamakonsu wannan ba aikinsa ba ne, idan Allah ya ga dama yana iya nuna masa wani nauʾi na azabar da ya yi musu tanadi tun a nan duniya, idan kuma ya ga dama yana iya karɓar ransa ba tare da ya ga irin azabar da za ta same su ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya faɗakar da kafirai da cewa, shin ba su ga yadda Allah yake ba wa Musulmi nasara a kansu ba, suna ta cinye garuruwansu da yaƙi, Musulunci kuma yana ta ƙara ƙarfi da yawa a garuruwansu? Allah ne mai yin hukunci tsakanin bayinsa da abin da ya ga dama, babu kuma mai warware hukuncin ko ya canja masa shi, kuma shi mai saurin yin hisabi ne ga mutanen farko da na ƙarshe a yini ɗaya kacal.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rarrashi Annabi (ﷺ) da cewa, kada ya damu da irin makirci da ƙulle-ƙullen da kafirai suke yi masa, ba za su taɓa yin nasara ba, domin kafiran da suka gabace su su ma sun ƙulla makirci ga annabawansu sun ƙaryata su, amma wannan bai yi wani tasiri ba ko kaɗan, domin makirci mai tasiri na ga Allah shi kaɗai, hakanan shi kaɗai ne ya san abin da suke aikatawa kuma zai yi musu sakayya a kai, a lokacin za su gane irin babban kuren da suka tabka na rashin ba da gaskiya da suka yi, za su gane lalle muminai su ne masu gaskiya, su ne kuma masu rabauta da gidan Aljanna.
Sai kuma a ayar ƙarshe ta wannan surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci maganar da kafirai suke faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, shi ba Manzon Allah ba ne, watau suna ƙaryata daʾawarsa ta manzanci. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya ba su amsa da cewa, Allah ya isa shaida tsakaninsa da su a kan cewa, shi Manzonsa ne, domin kuwa ya yi masa wahayi da yake tabbatar da haka, ya kuma ba shi goyon baya da nasara a kan abokan gabarsa, sannan ya tabbatar da daʾawarsa bai ƙaryata shi ba. Hakanan kuma ga shaidar waɗanda suke da ilimin littattafan da Allah ya saukar, watau cikin malaman maʾabota littafi waɗanda suka musulunta, sun shaida da manzancinsa har ma sun yi imani da shi. Waɗanda kuwa suka ƙaryata shi daga cikin malaman Yahudu da Nasara sun yi haka ne saboda girman kai amma a zuciyarsu sun san shi Manzon Allah ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Manufar saukar da Alƙurʾani ita ce, shiryar da mutane da fitar da su daga duhun ƙarya zuwa hasken gaskiya.

2. Shiriya ba ta samuwa ga kowa sai da izinin Allah.

3. Allah ya siffanta kansa a wannan ayar (ta 1) da cewa shi ne mabuwayi sha-yabo, a kan ayyukansa da maganganunsa. Wannan kuwa nuni ne ga cewa, duk wanda ya bi hanyar Allah ya riƙe Alƙurʾani to shi ne mai samun ɗaukaka da izza daga Allah ko da kuwa ba shi da mataimaka cikin mutane.

4. Sukan mutanen da suke fifita jin daɗin rayuwar duniya a kan niʾimomin lahira, kuma masu hana mutane bin hanyar Allah ta hanyar ɓata ta a idon jamaʾa da jefa musu ƙyamarta a zukatansu.

5. Allah ya aiko da kowane annabi da harshen mutanensa domin su fahimce shi su kuma karɓi abin da ya zo musu da shi.

6. Kasancewar Manzon Allah (ﷺ) an aiko shi da harshen mutanensa Larabci ba yana nuna shi Manzo ne ga Larabawa kaɗai ba, Manzancinsa ya game kowa da kowa mutum da aljan.

7. Wajibi ne a kan kowane Musulmi ya san harshen Larabci gwargwadon abin da zai buƙata domin gyara addininsa.

14-Suratu Ibrahim

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna: ***"Suratu Ibrahim"***. An jingina ta zuwa ga Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Wasu malamai sun ce abin da ya sa aka ambace ta da sunan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) saboda ta zo da bayanin wasu addu'o'i ne da ya yi. Wasu ma daga cikin abubuwan da ya roƙa a cikin waɗannan addu'o'i ba su auku ba sai bayan aiko Annabi (ﷺ) kamar farlanta Hajji da kuma sanya Ka'aba ta zama alƙiblar Musulmi.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce Makkiyya, wato ta sauka kafin Hijra, a bisa maganar ɗaukacin malamai. Amma Imamu Ƙatadatu yana ganin akwai ayoyi uku saukakkun Madina ne, su ne aya ta (28) da ta (29) da ta (30).

3. Jerin Saukarta:
A jerin saukar surori ita ce ta saba'in da biyu (72). Ta sauka bayan "*Suratus Shura*", kafin "*Suratul* Anbiya'".

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta a lissafi na mutanen Kufa hamsin da biyu (52) ne kamar yadda yake rubuce a cikin *Mus'hafi*. Amma a lissafin mutanen Basra ayoyinta hamsin da ɗaya ne (51). A wurin mutanen Madina kuwa sun ce hamsin da huɗu ne (54). A lissafin mutanen Sham kuma hamsin da biyar (55).

5. Babban Jigonta:
Karantar da Tauhidi da tabbatar da manzanci da kuma tabbatar da rayuwa bayan mutuwa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin mu'ujizar Alƙur'ani da girman sha'aninsa da kasancewarsa shiriya ga mutane.
• Saukar da Alƙur'ani cikin harshen Larabci da girmama Allah wanda ya saukar da shi da bayanin narkonsa da azabarsa ga waɗanda suka kafirce masa.
• Sanar da kafirai cewa Annabi (ﷺ) ba farau ne ba a cikin manzanni. Kuma don ya zamo mutum ba shi zai hana shi zama manzo ba, kamar sauran manzanni.
• Bayanin aiko Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga Fir'auna da Banu Isra'ila, da tunatar da su ni'imar Allah gare su don su gode masa da tsoratar da su irin azabar da ta sami mutanen Annabi Nuhu da Adawa da waɗanda suka gabace su.
• Bayanin tashi bayan mutuwa da gargaɗin kafirai da su nisanci ruɗin shugabanninsu gare su, domin a ranar alƙiyama za su nesanta kansu da su.
• Bayanin falalar Kalmar Shahada, da kuma munin kalmar kafirci.
• Bayyana mamaki ga mutanen da suka butulce wa ni'imar Ubangiji sannan suka jefa waɗanda suka bi su cikin halaka ta hanyar tsunduma su cikin shirka da saɓon Allah, tare da bayanin yadda su kuma muminai halinsu ya saɓa da wannan.

• Tunatarwa ga muminai da kafirai dangane da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), don su gane cewa, a cikinsu wane ne yake bin tafarkinsa da gaske, wane ne kuma ya kauce wa hanyarsa? Da sauran misalai da suka zo cikin wannan Sura.

Suratu Ibrahim (1-4)

الٓرۚ كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ إِلَيۡكَ لِتُخۡرِجَ ٱلنَّاسَ مِنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ بِإِذۡنِ رَبِّهِمۡ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَمِيدِ ١ ٱللَّهِ ٱلَّذِي لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا
فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَوَيۡلٞ لِّلۡكَٰفِرِينَ مِنۡ عَذَابٖ شَدِيدٍ ٢ ٱلَّذِينَ يَسۡتَحِبُّونَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا عَلَى ٱلۡأٓخِرَةِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَيَبۡغُونَهَا عِوَجٗاۚ
أُوْلَٰٓئِكَ فِي ضَلَٰلِۢ بَعِيدٖ ٣ وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن رَّسُولٍ إِلَّا بِلِسَانِ قَوۡمِهِۦ لِيُبَيِّنَ لَهُمۡۖ فَيُضِلُّ ٱللَّهُ مَن يَشَآءُ وَيَهۡدِي مَن يَشَآءُۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ALIF LAM RA.

Littafi ne da Muka saukar maka da shi, don ka fitar da mutane daga duffai zuwa ga haske, da izinin Ubangijinsu zuwa ga tafarkin (Allah) Mabuwayi, Abin godiya.

2. (Watau) Allah, Wanda abin da yake cikin sammai da na cikin ƙasa duka nasa ne. Bone na wata azaba mai tsanani kuma ya tabbatta ga kafirai.

3. Waɗanda suke fifita son rayuwar duniya a kan lahira, suke kuma hanawa (a bi) hanyar Allah, kuma suke neman ta zama karkatacciya. To waɗannan suna cikin ɓata mai nisa.

4. Ba Mu taɓa aiko wani manzo ba kuwa sai da harshen mutanensa don ya yi musu bayani; sannan Allah Yana ɓatar da wanda ya ga dama, ya kuma shiryar da wanda ya ga dama. Shi ne kuwa Mabuwayi, Mai hikima.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da haruffa irin yadda ya buɗe wasu surorin da suka gabata. Mun yi bayani a kansu. [Duba farkon *Suratul Baƙara*].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya saukar da wannan Littafi Alƙur'ani ga Manzonsa (ﷺ) domin ya fitar da mutane daga duhun kafirci da na jahilci da ɓata zuwa ga hasken imani da ilimi da shiriya. Watau zuwa ga addinin Musulunci wanda shi ne hanyar Allah mabuwayi wanda babu mai rinjayarsa, sha-yabo a kan duk ayyukansa da maganganunsa da shari'arsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da kafirai waɗanda suka ƙi miƙa wuya ga umarninsa, ya tabbatar musu da cewa, shi ne kaɗai Allah mamallakin abin da yake bayan ƙasa, don haka shi kaɗai ya cancanta a bauta wa, kada a haɗa shi da komai. Saboda haka tsananin azaba ya tabbata ga kafirai waɗanda ba sa ganin girman Allah ba sa bin umarninsa, suna kuma fifita rayuwar duniya mai gushewa a kan ta lahira mai ɗorewa. Ba su tsaya nan ba; sun kuma riƙa kautar da mutane daga hanyar Allah, kuma suna ƙoƙarin su gan ta a karkace don su jefa tsanarta a zukatan mutane har ya zamanto babu mai son bin ta ko riƙo da ita. Allah ya bayyana cewa, duk waɗanda suka siffantu da waɗannan siffofi to suna cikin wani ɓata mai nisa da gaskiya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin rahama da baiwa da ya yi wa bayinsa wajen aiko musu da manzanni, su kuma ya aiko su da harshen mutanensu don su samu saukin yi musu bayanin abin da Allah ya aiko su da shi. Su ma kuma mutanen su ji saukin fahimtar su, don kuma hujjar Allah ta tsaya a kansu, don haka Allah ya ɓatar da wanda ya ga dama da adalcinsa, ya kuma shiryar da wanda ya ga damar shiryar da shi da falalarsa. Shi ne kuma mabuwayi wanda babu mai iya rinjayar sa a kan halittarsa ko tsarinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babban aikin manzanni shi ne fitar da mutane daga duhun ƙarya zuwa ga hasken gaskiya.

2. Daga cikin hanyoyin kira zuwa ga Allah akwai tunatar da mutane ni'imomin da Allah ya yi musu, musamman idan ni'imomi ne manya-manya, kamar ba su nasara a kan abokan gabarsu ko tserar da su daga gare su.

3. Hikimar da take ƙunshe a cikin tunatar da mutane tarihin al'ummun da suka gabata shi ne, kwaɗaitar da su a kan kyawawan ayyuka da tsoratar da su munana.

4. Karanta tarihin al'ummun da suka gabata yana daga cikin hanyoyin ƙarfafa imani da haɓaka shi.

5. Godiya ga Allah a kan ni'imominsa tana sa Allah ya dawwamar da su ya kuma ƙara wa bawa wasu sababbi. Godiya ga Allah tana tabbata ne ta hanyar iƙirarin bawa da cewa,, wannan ni'imar daga Allah ne sannan da sanya ta inda ya dace da yardar Allah da shari'arsa.

6. Ishara ga mumini a kan cewa, wajibi ne a rayuwarsa ta duniya ya zamanto ko da yaushe mai haƙuri kuma mai godiya; domin yakan zamanto ko dai yana cikin wata musiba da zai yi haƙuri a kanta, ko kuma cikin wata ni'ima da zai yi godiya a kanta.

7. Kafircin bayi ba zai cutar da Allah da komai ba, kamar yadda imaninsu ba zai ƙare shi da komai ba.

Suratu Ibrahim (5-8)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَآ أَنۡ أَخۡرِجۡ قَوۡمَكَ مِنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ وَذَكِّرۡهُم بِأَيَّٰمِ ٱللَّهِۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّكُلِّ صَبَّارٖ شَكُورٖ ۝٥ وَإِذۡ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوۡمِهِ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَةَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ إِذۡ أَنجَىٰكُم مِّنۡ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ يَسُومُونَكُمۡ سُوٓءَ ٱلۡعَذَابِ وَيُذَبِّحُونَ أَبۡنَآءَكُمۡ وَيَسۡتَحۡيُونَ نِسَآءَكُمۡۚ وَفِي ذَٰلِكُم بَلَآءٞ مِّن رَّبِّكُمۡ عَظِيمٞ ۝٦ وَإِذۡ تَأَذَّنَ رَبُّكُمۡ لَئِن شَكَرۡتُمۡ لَأَزِيدَنَّكُمۡۖ وَلَئِن كَفَرۡتُمۡ إِنَّ عَذَابِي لَشَدِيدٞ ۝٧ وَقَالَ مُوسَىٰٓ إِن تَكۡفُرُوٓاْ أَنتُمۡ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا فَإِنَّ ٱللَّهَ لَغَنِيٌّ حَمِيدٌ ۝٨

5. Haƙiƙa kuma Mun aiko Musa da ayoyinmu cewa: "Ka fitar da mutananka daga duffai zuwa ga haske, kuma ka tunatar da su ni'imomin Allah (da ya yi musu)." Lalle game da wannan da akwai ayoyi ga duk wani mai yawan haƙuri, mai yawan godiya.

6. Kuma (ka tuna) lokacin da Musa ya ce da mutanensa: "Ku tuna ni'imar Allah a gare ku lokacin da Ya tserar da ku daga mutanen Fir'auna, suna gana muku azaba, suna kuma yanyanka 'ya'yanku, kuma suna raya matayenku. A game da wannan da akwai bala'i mai girma daga Ubangijinku.

7. "Kuma (ku tuna) lokacin da Ubangijinku ya sanar da ku: "Lalle idan kuka gode wa (ni'imata) tabbas zan ƙara muku; idan kuwa kuka butulce, to lalle azabata tabbas mai tsanani ce."

8. Musa kuma ya ce: "Idan kuka kafirce, ku da waɗanda suke a bayan ƙasa baki ɗaya, to lalle Allah tabbas Mawadaci ne, Sha-yabo."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya aiko Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kuma ƙarfafe shi da wasu mu'ujizoji waɗanda suke tabbatar da gaskiyar manzancinsa, kuma ya umarce shi da ya fitar da mutanensa daga duhun kafirci da jahilci da ɓata zuwa ga hasken imani da ilimi da shiriya. Hakanan ya tunatar da Banu Isra'ila game da wasu kwanaki da suka shuɗe a rayuwarsu da Allah ya yi musu ni'imomi masu yawa a cikinsu. A cikin waɗannan tabbas kwanakin akwai ƙwararan dalilai masu nuna Ɗayantakar Allah da girman ikonsa da ni'imominsa ga muminai. Waɗannan duka ayoyi ne ga duk wani mai yawan haƙuri bisa ɗa'a ga Allah da juriya a kan abin da zai same shi na ɓacin rai da tashin hankali, mai yawan godiya game da ni'imomin Allah gare shi.

An karɓo daga Suhaibu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Akwai abin mamaki ga al'amarin mumini, al'amarinsa duka alheri ne, babu kuma mai samun haka sai mumini. Idan wani abin farin ciki ya same shi sai ya gode, sai ya zama alheri gare shi; idan kuma wata cuta ta same shi sai ya yi haƙuri sai ya zama alheri gare shi." [Muslim #2999].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa cewa, ya tuna lokacin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bi umarnin Allah, ya tunatar da mutanensa ni'imomin da Allah ya yi musu a tarihin rayuwarsu, lokacin da ya kuɓutar da su daga sharrin Fir'auna da jama'arsa, lokacin da suke ɗandana musu azaba iri-iri suna nuna musu wulaƙanci daban-daban wanda ya kai har suna yanka 'ya'yansu maza jarirai don gudun kada a haifo wanda zai ƙwace wa Fir'auna mulkinsa. Sai kuma su ƙyale 'ya'yansu mata domin su riƙa yi musu bauta a gidajensu, suna saka su ayyukan ƙasƙanci da tozartawa. Allah ya bayyana cewa, a cikin wannan yanayi da Banu Isra'ila suka tsinci kansu a mulkin Fir'auna lalle akwai babbar jarrabawa gare su. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuɓutar da su sakamakon haƙurin da suka yi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana mana cewa, Annabi Musa ya shelanta wa mutanensa da babbar murya don kowa ya ji cewa,, idan suka yi wa Allah godiya a kan ni'imomin can da ya yi musu, to lalle tabbas zai ƙara musu ni'imominsa da falalarsa, amma idan suka butulce wa ni'imominsa suka ƙi godiya, to su sani cewa, lalle azabarsa mai tsanani ce.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya bayyana wa mutanensa cewa,, idan da a ce za su kafirce wa Allah tare da duk waɗanda suke bayan ƙasa, to kawunansu suka cuta ba Allah ba, domin shi mawadaci ne da Zatinsa ba ya da buƙatar komai a wurin kowa, kuma sha-yabo ne saboda kyawawan ayyukansa; don haka imanin masu imani ba zai ƙare shi da komai ba, hakanan kafircin kafirai ba zai cuce shi da komai ba.

An karɓo daga Abu Zarrin Al-Ghifari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: Allah ya ce: "Ya ku bayina, da a ce na farkonku da na ƙarshenku da mutanenku da aljannunku; zukatansu za su zamanto kamar zuciyar wanda ya fi kowa taƙawa daga cikinku (shi ne Annabi Muhammadu), wannan ba zai ƙara komai a cikin mulkina ba. Ya ku bayina, da a ce na farkonku da na ƙarshenku da mutanenku da aljannunku; zukatansu za su zamanto kamar zuciyar wanda ya fi kowa fajirci daga cikinku (shi ne Iblis), to wannan ba zai tauye komai daga cikin mulkina ba…" [Muslim #2577].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yayin da ya zamanto sau tari wanda yake kwaɗaitarwa a kan wani aiki, yake kuma ba da kyakkyawan sakamako ga wanda ya aikata shi, ko yake hana aikata wani abu har yake yin uƙuba ga wanda ya aikata shi, lalle ana yi masa zaton yana da wata masalaharsa a cikin wannan abu, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi babu wata cuta da za ta iya samun sa ko wani amfani da zai samu daga wurin wani mahaluƙi; wannan duk al'amari ne da ya shafi bawa shi kaɗai.

2. Da yawa daga cikin kafirai suna tsammanin idan sun yi imani da Allah, to sun taimaka masa ne, kuma annabawa da suke matsa musu sai sun yi imani suna yin haka ne don ƙara wa kawunansu wani matsayi, ko tabbatar wa da kawunansu wata masalaha. Lokacin da Allah ya yi musu alƙawarin ƙari idan sun yi godiya, ya kuma yi musu narko da azaba idan sun yi butulci, sai aka guji wannan hasashen nasu ya ƙara ƙarfi sai Allah ya bayyana musu cewa, shi mai cikakkiyar wadata ne ba ya da wata buƙata a wurin kowa.

3. Annabawa da manzanni su ma mutane ne daga cikin ‘ya’yan Annabi Adamu, sai dai Allah ya fifita su, ya zaɓe su don su zama annabawansa da manzanninsa zuwa ga sauran mutane.

4. Wajibi ne duk wani mai kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya a ransa za a iya cutar da shi saboda wannan aiki nasa, don haka ya shirya yin haƙuri da juriya a kan abin da zai same shi.

5. Annabawa suna yin tawakkali da Allah a matakinsa mafi daraja, watau tawakkali wajen yaɗa addinin Allah da shiryar da bayinsa ga hanya madaidaiciya da kuɓutar da su daga ɓata da jahilci.

6. Daga cikin manyan abubuwa da suka wajaba a kan mai kira zuwa ga Allah akwai dogaro ga Allah da kuma sakankancewa da alƙawarin Allah na samun nasara a rayuwa.

Suratu Ibrahim (9-12)

أَلَمۡ يَأۡتِكُمۡ نَبَؤُاْ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ قَوۡمِ نُوحٖ وَعَادٖ وَثَمُودَ وَٱلَّذِينَ مِنۢ بَعۡدِهِمۡ لَا يَعۡلَمُهُمۡ إِلَّا ٱللَّهُۚ جَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَرَدُّوٓاْ أَيۡدِيَهُمۡ فِيٓ أَفۡوَٰهِهِمۡ وَقَالُوٓاْ إِنَّا كَفَرۡنَا بِمَآ أُرۡسِلۡتُم بِهِۦ وَإِنَّا لَفِي شَكّٖ مِّمَّا تَدۡعُونَنَآ إِلَيۡهِ مُرِيبٖ ٩ قَالَتۡ رُسُلُهُمۡ أَفِي ٱللَّهِ شَكٌّ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ يَدۡعُوكُمۡ لِيَغۡفِرَ لَكُم مِّن ذُنُوبِكُمۡ وَيُؤَخِّرَكُمۡ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمًّىۚ قَالُوٓاْ إِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُنَا تُرِيدُونَ أَن تَصُدُّونَا عَمَّا كَانَ يَعۡبُدُ ءَابَآؤُنَا فَأۡتُونَا بِسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٖ ١٠ قَالَتۡ لَهُمۡ رُسُلُهُمۡ إِن نَّحۡنُ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَمُنُّ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۖ وَمَا كَانَ لَنَآ أَن نَّأۡتِيَكُم بِسُلۡطَٰنٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١١ وَمَا لَنَآ أَلَّا نَتَوَكَّلَ عَلَى ٱللَّهِ وَقَدۡ هَدَىٰنَا سُبُلَنَاۚ وَلَنَصۡبِرَنَّ عَلَىٰ مَآ ءَاذَيۡتُمُونَاۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُتَوَكِّلُونَ ١٢

9. Wai yanzu labarin waɗanda suka gabace ku bai zo muku ba na mutanen Nuhu da Adawa da Samudawa da waɗanda (suka zo) daga bayansu? Ba wanda ya san iyakarsu sai Allah. Manzanninsu sun zo musu da hujjoji bayyanannu, amma sai suka riƙa cizon hannayensu (saboda haushi), suka kuma ce: “Lalle mu kam mun kafirta da abin da aka aiko ku da shi, lalle kuma muna cikin matuƙar shakka game abin da kuke kiran mu zuwa gare shi.”

10. Mazanninsu suka ce: “Yanzu kuwa ashe akwai wata shakka game da Allah, Maƙagin sammai da ƙasa? Yana kiran ku ne don ya gafarta muku zunubanku kuma ya saurara muku har zuwa wani lokaci ƙayyadajje.” Suka ce: “Ku ba wasu ba ne daban in ban da mutane kamar mu, kuna so ne ku hana mu bin abin da iyanenmu suka kasance suna bauta wa, to sai ku kawo mana hujjoji bayyanannu.”

11. Manzanninsu suka ce: “Mu ba kowa ba ne in ban da mutane kamarku, sai dai Allah Yana yin baiwa ga wanda Ya ga dama ne daga bayinsa, kuma ba zai yiwu ba a gare mu mu zo muku da wata hujja sai dai da izinin Allah. Muminai kuwa lalle su dogara ga Allah kawai.

12. “Kuma me zai hana mu mu dogara ga Allah, alhali kuwa haƙiƙa Ya shiryar da mu hanyoyinmu? Lalle kuwa tabbas za mu yi haƙuri bisa irin cutar mu da kuka yi. Masu dogaro kuma sai su dogara ga Allah kaɗai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tambayar kafiran Ƙuraishawa da ire-irensu cewa,, ba su samu labarin al'ummun da suka gabace su ba waɗanda suka ƙaryata manzanninsu, kamar mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Samudawa mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ma wasu al'ummu masu yawan da babu wanda ya san adadinsu sai Allah. Dukkansu manzanninsu sun zo musu da hujjoji bayyanannu, to amma sai suka riƙa sanya hannayensu suna rufe bakunansu, watau suna cizon yatsunsu saboda haushin manzanninsu da ya cika musu zukata. Kai sun ma fito fili suna sanar da manzanninsu cewa, su fa sun kafirce wa duk abin da aka aiko su da shi, suna kuma shakkar abin da suke kiran su zuwa gare shi.
Sai manzanninsu suka amsa musu da cewa,, yanzu akwai abin da za su yi shakkarsa dangane da shaʾanin kaɗaita Allah da bauta, duk da hujjoji masu yawa da ke kewaye da su a kan cancantarsa ga hakan? Cikinsu akwai cewa shi ne wanda ya ƙirƙiri halittar sammai da ƙasa ba tare da wani ya riga shi ba, sannan kuma abin mamaki, har ila-yau, shi ne sun riƙa shakka game da abin da manzannin nan suka zo musu da shi duk da cewa, abu ne mai matuƙar amfani gare su, watau kiran su zuwa ga yin imani da Allah domin ya gafarta musu zunuban da suka yi, kuma ya jinkirta musu har zuwa ƙarshen lokacin da aka yanka musu na rayuwarsu ta duniya. To amma duk da wannan jawabin da manzannin suka yi musu, sai mushirikai suka sake fito da wata maganar marar tushe, suka soki manzannin da cewa, ai su mutane ne kamarsu ba su da wani abin da suka fi su da shi da har zai sa Allah ya zaɓe su ya aiko su, kawai dai suna so ne su raba su da bautar abin da iyayensu suka kasance suna bauta wa. Kuma suka nemi manzannin nan su kawo musu wata hujja da za su gamsu da ita ta cewar su manzannin Allah ne na gaskiya.
Sai waɗannan manzanni suka yarda cewa, su mutane ne kamarsu a halitta, sai dai hakan ba yana nuna sun yi kama da su ne ta kowace nahiya ba, domin su kansu su san cewa, Allah yana keɓe wanda ya ga dama da wata niʾima tasa ta musamman, don haka ne ya zaɓo su daga cikin mutane ya ba su manzanci. To amma batun hujja kuwa, su kafirai suna nufin irin muʾujizoji da suke neman sai an nuna musu kafin su yarda da gaskiyar manzanninsu, sai manzannin suka faɗa musu cewa, aikata haka ba ya hannunsu; yana hannun Allah ne, kuma da izininsa za su iya nuna musu wannan hujjar da suke buƙata. Don haka muminai suna dogaro ga Allah ne shi kaɗai cikin duk wani lamarinsu.
Suka sake jaddada musu cewa, ba su da wani uzuri da zai hana su dogaro da Allah, alhali shi ne ya ɗora su a kan miƙaƙƙiyar hanyar da suka bi. Sannan sun tabbata da cewa kafirai ba za su ƙyale su ba, za su ci gaba da cutar da su da yi musu izgili da ƙaryata su, to su a shirye suke su yi haƙuri a kan duk waɗannan abubuwa. Kuma gare shi za su ci gaba da dogaro, domin da man gare shi masu dogaro suke dogara cikin duk lamarinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alʾada ce ta marar gaskiya a koyaushe ya rasa hujjar da zai bayar don kare raʾayinsa sai ya koma ɗaukar matakin faɗa tare da barazanar amfani da ƙarfi.
2. Tsananin zaluncin kafirai ga manzanninsu, domin ba su tsaya a kan ƙaryata su ba da bijire wa shiriyar da suka zo musu da ita ba, sai da suka ƙara da barazanar za su kore su daga ƙasarsu, da cewa, ƙasar ma tasu ce su kaɗai, manzanni ba su da haƙƙin zama a cikinta, duk kuwa da cewa nan ce mahaifar iyayensu da kakanninsu.

3. Daidai laifi daidai sakamako. Yayin da kafirai suka yi barazanar korar manzannin Allah daga ƙasashensu na haihuwa, sai shi kuma Allah ya yi musu barazanar hallakar da su gaba ɗaya, daga doron ƙasa, wanda yin hakan ya ma fi kora da suke yi wa manzannin barazana da ita, domin su manzannin za su iya komawa ƙasarsu ko da an kore su, amma waɗanda aka hallakar an kawar da su ne baki ɗaya daga doron ƙasa babu komawa har abada.

4. Sharaɗìn samun nasara da kafuwa a bayan ƙasa shi ne tabbatar da tsoron Allah da kiyaye dokokinsa.

5. ‘Yan wuta masu dawwama ne a cikin azabarta babu mutuwa har abada.

Suratu Ibrahim (13-17)

وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لِرُسُلِهِمۡ لَنُخۡرِجَنَّكُم مِّنۡ أَرۡضِنَآ أَوۡ لَتَعُودُنَّ فِي مِلَّتِنَاۖ فَأَوۡحَىٰٓ إِلَيۡهِمۡ رَبُّهُمۡ لَنُهۡلِكَنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٣ وَلَنُسۡكِنَنَّكُمُ ٱلۡأَرۡضَ مِنۢ بَعۡدِهِمۡۚ ذَٰلِكَ لِمَنۡ خَافَ مَقَامِي وَخَافَ وَعِيدِ ١٤ وَٱسۡتَفۡتَحُواْ وَخَابَ كُلُّ جَبَّارٍ عَنِيدٖ ١٥ مِّن وَرَآئِهِۦ جَهَنَّمُ وَيُسۡقَىٰ مِن مَّآءٖ صَدِيدٖ ١٦ يَتَجَرَّعُهُۥ وَلَا يَكَادُ يُسِيغُهُۥ وَيَأۡتِيهِ ٱلۡمَوۡتُ مِن كُلِّ مَكَانٖ وَمَا هُوَ بِمَيِّتٖۖ وَمِن وَرَآئِهِۦ عَذَابٌ غَلِيظٞ ١٧

13. Waɗanda suka kafirta kuma suka ce da manzanninsu: “Lalle ba makawa za mu fitar da ku daga ƙasarmu, ko kuwa lalle ku komo cikin addininmu. Sai Ubangijinsu ya aiko musu cewa: “Lalle za Mu hallaka azzalumai.

14. “Kuma tabbas za mu zaunar da ku ƙasar (tasu) a bayansu. Wannan kuwa sai ga wanda ya ji tsoron tsayuwa a gabana ya kuma ji tsoron narkona.”

15. Sai kuma (manzannin) suka nemi nasarar (Allah), kuma (a ƙarshenta) duk wani mai nuna isa mai taurin kai ya hallaka.

16. A gabansa Jahannama ce (take jiran sa), za a kuma shayar da shi ruwan mugunya.

17. Yana kwankwaɗar sa, ba kuwa zai ji daɗìn haɗìyarsa ba, mutuwa kuma za ta zo masa ko ta ina, ba kuwa zai mutu ba; kuma a gabansa ga azaba mai kauri.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani irin mummunan mataki da kafirai suka shirya ɗauka a kan manzanninsu bayan sun kasa bayyana musu wani ƙwaƙƙwaran dalilin da ya sa suka kafirce wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) suka ƙaryata su. Sai kafiran suka yi barazanar korar manzannin daga ƙasarsu, in ba haka ba kuwa su manzannin su dawo cikin addinin waɗannan kafirai. To amma Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafi manzannin ta hanyar yi musu wahayi da cewa, lalle zai hallaka waɗannan kafirai saboda zaluncinsu na yi wa Allah shirka da ƙaryata manzanninsa da cutar da su, ya kuma yi wa manzannin alƙawarin mallaka musu wannan ƙasar don ci gaba da zama a cikinta su da mabiyansu bayan ya hallaka kafirai. To amma sai da ya bayyana sharuɗɗan zartar da wannan alƙawari da cewa, guda biyu ne: Na farko, halarto da girman Allah da tsoron tsayawa a gabansa. Na biyu; tsoron narkon azabarsa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa,, manzanni sun nemi taimakon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ba su nasara a kan abokan gabarsu. Allah kuma ya nufi duk wani kafiri mai nuna isa da mai taurin kai ya yi hasara duniya da lahira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana mafi munin hasara da taɓewa da kafiri zai gamu da ita ranar alƙiyama, domin kuwa Jahannama ce take jiran sa, sannan a shayar da shi mugunyar ‘yan wuta, watau ruwan da yake fitowa daga gyambonsu. Shi za su yi ta kwankwaɗa ba tare da yana kashe musu ƙishi ba, kuma za su ci gaba da zama cikin azabar ƙishirwa da wasu dangogin azaba daban-daban. Mutuwa kuma ta yi ta zo masa ta ko’ina, saboda tsananin azabar da yake ɗanɗana, to amma ba zai samu ya mutu ba ballantana ya huta da azabar. Bayan wannan azabar kuma a gabansa akwai wata matsananciyar azabar tana jiran sa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafiri ba zai amfana da kyawawan ayyukansa ba a ranar lahira saboda kafircinsa da rashin yin imani da Allah da Manzonsa.

2. Duk wanda ya yi nisa a cikin ɓata ya rabu da Allah, to ba zai amfana da yin duba a cikin ayoyin Allah ba waɗanda suke nuna Kaɗaitarsa da cikar Ƙudirarsa duk da cewa, ga su nan a fili ƙarara kowa yana gani.

3. Kamar yadda kyawawan ayyukan kafirai ba za su amfane su da komai a ranar lahira ba, to hakanan ayyukan da suke yi a nan duniya don ƙulla wa muminai makirci da yunƙurin gusar da gaskiya, su ma ba za su amfane su da komai ba; za su yi ta wahala ne tuƙuri a kan haka, daga ƙarshe gaskiya ce za ta yi nasara ƙarya kuwa ta faɗi warwas.

Suratu Ibrahim (18-20)

مَّثَلُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمۡۖ أَعۡمَٰلُهُمۡ كَرَمَادٍ ٱشۡتَدَّتۡ بِهِ ٱلرِّيحُ فِي يَوۡمٍ عَاصِفٖۖ لَّا يَقۡدِرُونَ مِمَّا كَسَبُواْ عَلَىٰ شَيۡءٖۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلضَّلَٰلُ ٱلۡبَعِيدُ ١٨
أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّۚ إِن يَشَأۡ يُذۡهِبۡكُمۡ وَيَأۡتِ بِخَلۡقٖ جَدِيدٖ ١٩ وَمَا ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ بِعَزِيزٖ ٢٠

18. Misalin waɗanda suka kafirce wa Ubangijinsu; ayyukansu sun yi kama da toka wadda iska mai tsananin ƙarfi ta kwasa a wata rana mai guguwa; ba za su sami iko a kan komai ba dangane da abin da suka aikata (na kirki). Wannan shi ne ɓata mai nisa.

19. Ashe ba ka ga cewa, lalle Allah Ya halicci sammai da ƙasa kan gaskiya ba? Idan Ya ga dama sai Ya hallakar da ku Ya kuma zo da wata halitta sabuwa.

20. Wannan kuwa ba abin da zai gagari Allah ba ne.

A waɗannan ayoyi, bayan Allah ya bayyana irin mummunar azabar da take jiran kafirai, sai kuma ya bayyana cewa, duk yawan kyawawan ayyuka da za su yi a nan duniya ba za su amfane su da komai a ranar alƙiyama ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwatanta ayyukansu da toka wadda wata guguwa za ta taso da ƙarfi ta kwashe ta ta ɗaiɗaita ta a cikin iska ta warwatse a koʼina, babu mai iya harhaɗo ta wuri guda don ta yi wani amfani. To haka kyawawan ayyukan kafirai za su kasance a ranar alƙiyama, ba za su ga komai ba daga cikinsu ballantana su amfana da su.

An karɓo daga Aʼisha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Na ce wa Manzon Allah (ﷺ): "Ya Manzon Allah, Ibnu Judʼan ya kasance a zamanin jahiliyya yana sada zumunci yana ciyar da mabuƙata, shin wannan zai amfane shi?" Sai Manzon Allah ya ce: "Aʼa, ba zai amfane shi ba, domin babu wata rana da ya taɓa cewa,: "Ya Allah ka gafarta mini kurakuraina a ranar sakamako." [Muslim #214].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, wannan ranar, watau alƙiyama, tana nan tafe babu makawa, domin kuwa duk wanda ya ƙagi halittar sammai da ƙasa ba tare da wani ya taimaka masa ba, to yana da cikakken ikon da zai hallaka su ya ƙagi wasu halittun daban, wannan ba wani aiki ne da zai gagare shi ba sam sam.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin mummunan ƙarshen mabiya da shugabanninsu waɗanda suka haɗu a kan ƙarya.

2. Babban abin da mushirikai za su yi da-na-sani a kansa a lahira shi ne, rashin bin shiriyar Allah a duniya. Don haka mumini ya yi ƙoƙarin riƙe shiriyar da ya samu gam-gam a duniya domin kada ya zo ya yi da-na-sani a lahira.

3. Mumini ya yi haƙuri ya jure wa biyayya ga Allah da barin saɓa masa tun kafin zuwan ranar da haƙuri ko raki ba za su yi amfani gare shi ba.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana huɗubar da Shaiɗan zai yi wa ‘yan wuta a cikin wuta ne domin ya ja hankalin masu sauraro a kan su yi tunani game da makomarsu a wannan rana, su yi mata kyakkyawan tanadi, su tuna ranar da Shaiɗan zai tsaya a gaban ‘yan wuta yana musu maganganun banza irin waɗannan, su ji tsoron yin aikin da zai kai su ga sauraron irin wannan muguwar huɗuba ta Iblis.

5. Shaiɗan ba shi da wata hujja a kan abin da ya ɗora mabiyansa a nan duniya. Ba abin da ya nuna musu in ban da ruɗani da ƙawata musu ƙarya don ya jefa musu shaʾawarta; da haka ne ya sami mabiyanshi masu yawa a duniya.

Suratu Ibrahim (21-23)

وَبَرَزُواْ لِلَّهِ جَمِيعًا فَقَالَ ٱلضُّعَفَٰٓؤُاْ لِلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُوٓاْ إِنَّا كُنَّا لَكُمۡ تَبَعٗا فَهَلۡ أَنتُم مُّغۡنُونَ عَنَّا مِنۡ عَذَابِ ٱللَّهِ مِن شَيۡءٖۚ قَالُواْ لَوۡ هَدَىٰنَا ٱللَّهُ لَهَدَيۡنَٰكُمۡۖ سَوَآءٌ عَلَيۡنَآ أَجَزِعۡنَآ أَمۡ صَبَرۡنَا مَا لَنَا مِن مَّحِيصٖ ٢١ وَقَالَ ٱلشَّيۡطَٰنُ لَمَّا قُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ إِنَّ ٱللَّهَ وَعَدَكُمۡ وَعۡدَ ٱلۡحَقِّ وَوَعَدتُّكُمۡ فَأَخۡلَفۡتُكُمۡۖ وَمَا كَانَ لِيَ عَلَيۡكُم مِّن سُلۡطَٰنٍ إِلَّآ أَن دَعَوۡتُكُمۡ فَٱسۡتَجَبۡتُمۡ لِيۖ فَلَا تَلُومُونِي وَلُومُوٓاْ أَنفُسَكُمۖ مَّآ أَنَا۠ بِمُصۡرِخِكُمۡ وَمَآ أَنتُم بِمُصۡرِخِيَّ إِنِّي كَفَرۡتُ بِمَآ أَشۡرَكۡتُمُونِ مِن قَبۡلُۗ إِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٢٢ وَأُدۡخِلَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا بِإِذۡنِ رَبِّهِمۡۖ تَحِيَّتُهُمۡ فِيهَا سَلَٰمٌ ٢٣

21. Suka kuma fito gaba ɗaya a gaban Allah (ranar alƙiyama), sai raunanan suka ce da waɗanda suka yi girman kai: “Lalle mu mun zamanto mabiya a gare ku, to ko za ku maganta mana wani abu daga azabar Allah?” Suka ce: “Da Allah Ya shirye mu da lalle mun shiryar da ku; duka ɗaya ne gare mu ko mun yi raki ko mun yi haƙuri (duka dai) ba mu da wata maguda.”

22. Shaiɗan kuma lokacin da aka gama hukunci ya ce: “Lalle Allah Ya yi muku alƙawari na gaskiya, ni kuma na yi muku alƙawari sai na saɓa muku. To ba ni da wani ƙarfi da na nuna muku, sai dai na yi kiran ku ne sai kuka amsa mini; to kada ku zarge ni, ku zargi kanku; ni ba zan taimake ku ba, ku kuma ba za ku taimake ni ba. Lalle ni na riga na kafirta da abin da kuka yi tarayya da ni a kansa tun a da can. Lalle azzalumai suna da (sakamakon) azaba mai raɗaɗi.”

23. Aka kuma shigar da waɗanda suka yi imani, suka kuma yi aiki nagari gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu da izinin Ubangijinsu; gaisuwarsu a cikinsu ita ce: “Aminci (ya tabbata a gare ku).”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar da mutane lokacin da za su fito gaba ɗaya daga ƙaburburansu, don ya yi musu hisabi, a kai kowa gidansa, a nan ne mabiya da shugabanninsu za su shiga musayar magana da junansu a wutar Jahannama. Mabiya su zargi shugabanninsu da cewa, su a duniya suna yi musu biyayya, suna aiki da umarninsu suna hanuwa da haninsu, to yau ga shi duk an haɗa su a wuta, shin yanzu za su iya ɗauke musu wannan azabar da suke ciki? Sai shugabannin su amsa musu da cewa, ai da Allah ya shiryar da su to da sun shiryu sun bi gaskiya gaba ɗaya sun kuɓuta daga azaba, to

amma sai suka ɓace, don haka suka ɓatar da mabiyansu. Suka ƙara musu da cewa, a yanzu kam bayan an gama hisabi har an saka su wutar Jahannama to duk wani raki da za su yi ko su yi haƙuri su jure wa azabar wuta, hakan ba shi da wani amfani a gare su, domin kuwa babu sauran wata maguda ko maɓoya da ta rage musu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, a nan ne Iblis zai miƙe shi kuma ya yi tasa huɗubar ga duk ‘yan wuta, ya fito fili ya tabbatar musu cewa ba a kan gaskiya ya ɗora su ba, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu alƙawarin gaskiya yayin da ya aiko musu da manzanni ya yi umarni da su bi su domin su sami tsira, amma sai suka ƙi imani da su, shi kuma sai ya yi musu alƙawarin ƙarya, ya nuna musu su bi shi za su rabauta. To a yau ga yadda al’amarin ya kwaɓe musu, domin ba su samu abin da ya yi musu alƙawari da shi ba. Ya bayyana musu cewa, shi fa a lokacin da yake kiran su zuwa ga ɓata ba wani ƙarfi yake nuna musu ba don su yi masa biyayya a kan kafirci da ɓata, kawai ya kira su ne zuwa kafirci, ya ƙawata musu saɓon Allah sai suka bi shi a kan haka; don haka a yau su daina zargin sa da ya ɓatar da su, su zargi kawunansu. Sannan ya tabbatar musu da cewa, shi ba zai iya taimakon su ya kare su daga azaba ba, su ma kuma ba za su iya taimaka masa da komai ba. Ya ƙara da cewa, shi lalle ya kafirce wa bautar da suka yi masa, yayin da suka sanya shi abokin tarayya da Allah a duniya, domin kuwa ya san azzalumai da suka haɗa Allah da wani wajen bauta suna da azaba mai raɗaɗi sakamakon aikinsu.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana makomar kafirai a ranar alƙiyama, sai kuma ya bayyana makomar muminai waɗanda suka yi imani kuma suka yi kyawawan ayyuka da cewa, za a shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su zauna a cikinsu zama na har abada da izinin Ubangijinsu. Za su riƙa gai da junansu, mala’iku ma za su riƙa yi musu gaisuwa da sallama, watau amincin Allah ya tabbata a gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kamanta Kalmar Shahada da daddaɗar bishiya mai maɗaukakan rassa, kuma mai tabbataccen tushe.

2. Kwatanta kalmar kafirci da bishiyar gunar shanu mai yaɗo a ƙasa ba tare da kafaffen tushe a cikin ƙasa ba, kuma ba mai rassa a sama ba, sannan ba ta yin ‘ya’ya masu daɗi sai masu tsananin ɗaci, ga shi kuma ba ta daɗewa a raye.

3. Tabbatar da tambayar ƙabari ga matattu, kuma mumini Allah zai tabbatar da shi, ya iya bayar da amsoshin tambayoyin da mala’iku biyu za su yi masa daidai ba tare da kuskure ba. Amma kafiri ko munafuki, zai daburce ya rasa abin faɗa yayin da ake yi masa tambayoyi, ya ce shi bai san amsar ba, bai karanta ba. Tun daga lokacin zai fara ɗandanar azaba har zuwa tashin alƙiyama.

4. Tabbata a kan shiriya yana kasancewa, ga mumini duniya da lahira, kuma wata ni’ima ce daga Allah; duk wanda ya tabbatar da shi a nan duniya to zai tabbatar da shi a lahira.

5. Zaluncin bawa ga kansa shi ne musabbabin ɓatansa, don haka wajibi ne mutum ya nisanci zalunci kowane iri ne don ya dace da shiriyar Allah.

Suratu Ibrahim (24-27)
أَلَمْ تَرَ كَيْفَ ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا كَلِمَةً طَيِّبَةً كَشَجَرَةٍ طَيِّبَةٍ أَصْلُهَا ثَابِتٌ وَفَرْعُهَا فِى ٱلسَّمَآءِ ﴿٢٤﴾ تُؤْتِىٓ أُكُلَهَا كُلَّ حِينٍۭ بِإِذْنِ رَبِّهَا ۗ وَيَضْرِبُ ٱللَّهُ ٱلْأَمْثَالَ لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٢٥﴾ وَمَثَلُ كَلِمَةٍ خَبِيثَةٍ كَشَجَرَةٍ خَبِيثَةٍ ٱجْتُثَّتْ مِن فَوْقِ ٱلْأَرْضِ مَا لَهَا مِن قَرَارٍ ﴿٢٦﴾ يُثَبِّتُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱلْقَوْلِ ٱلثَّابِتِ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَفِى ٱلْـَٔاخِرَةِ ۖ وَيُضِلُّ ٱللَّهُ ٱلظَّٰلِمِينَ ۚ وَيَفْعَلُ ٱللَّهُ مَا يَشَآءُ ﴿٢٧﴾

24. Shin ba ka ga yadda Allah Ya ba da misali ba? Daddaɗar kalma kamar daddaɗar bishiya ce wadda tushenta kafaffe ne (a ƙasa) reshenta kuma yana sama.

25. Tana bayar da ‘ya’yanta ko da yaushe da izinin Ubangijinta. Allah kuwa Yana ba da misalai ne ga mutane don su wa’azantu.

26. Misalin kuma mummunar kalma kamar mummunar bishiya ce da aka tumɓuke daga kan ƙasa, ba ta da wata matabbata.

27. Allah Yana tabbatar da waɗanda suka yi imani a kan magana tabbatacciya a rayuwar duniya da kuma a lahira; Yana kuma ɓatar da azzalumai. Allah kuma Yana aikata abin da Ya ga dama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwatanta Kalmar Shahada da wata bishiya wadda saiwoyinta suka kama ƙasa sosai, ressanta kuma suna sama, tana fitar da ‘ya’ya masu daɗi a ko da yaushe. Wannan ita ce shiriya lokacin da za ta shiga zuciyar mumini sannan ta yi naso ta kwarara a kan sauran gaɓoɓinsa, ta kuma cika wasu zukata masu yawa, ta haskaka su da haskenta, ta zama kamar bishiyar da take fitar da ‘ya’yanta masu daɗi kuma marasa yankewa ga kowa da kowa.
Da yawa daga cikin magabata na ƙwarai sun ce wannan kalma ita ce Kalmar Shahada, watau shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah. Bishiyar kuwa ita ce mumini. Kalmar Shahada tana kafa tushenta a cikin zuciyar mumini, da ita kuma ake ɗaukaka kyakkyawan aikinsa zuwa sama. An ruwaito cewa, wannan bishiyar mai kyau ita ce bishiyar dabino.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana muna zaune gaban Manzon Allah (ﷺ) sai ya ce: “Ku faɗa mini wacce bishiya ce mai kama da Musulmi wadda ganyenta ba ya kakkaɓewa a lokacin sanyi ko zafi, kuma take bayar da ‘ya’yanta ko da yaushe da izinin Ubangijinta?” Ɗan Umar ya ce: “Sai na ji a raina cewa, ita ce bishiyar dabino, to amma sai na ga Abubakar da Umar ba su ce komai ba, sai na ƙi yin magana tun da su ma ba su ce wa Manzon Allah komai ba.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ita ce bishiyar dabino.” [Bukhari #4689 da Muslim #2811].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwatanta kalmar kafirci da wata mummunar bishiya mai ‘ya’ya marasa daɗin ci, kuma marar amfani. An siffanta ta gunar shanu wadda aka tumɓuke ta daga kan ƙasa, watau ba ta da wasu saiwoyi a ƙasa da ke riƙe da ita, kuma ga shi ba ta da wasu ‘ya’ya masu daɗi ko amfani sai ‘ya’ya munana masu tsananin ɗaci. To kamar haka ita ma kalmar kafirci take a zuciya, ba ta da wani tushe tabbatacce, ba ta haifar da wani aiki ko magana mai kyau sai dai abin da zai cutar da mai ita, abin da ba shi da wani amfani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, zai tabbatar da muminai a kan kalmar Tauhidi a nan rayuwarsu ta duniya har su mutu a kanta. Hakanan da lokacin kwanciyarsu a cikin ƙabari da lokacin yi musu tambayar ƙabari, ya kuma tashe su da ita a ranar alƙiyama domin yi musu sakamako a kanta. To amma waɗanda suka zaɓi ɓata a kan shiriya, suka yarda da kafirci da shirka, suka zalunci kawunansu, to su Allah yana ɓatar da su, ya hana musu dace a rayuwar duniya da ta bayan mutuwa, domin Allah yana yin abin da ya ga dama, ya shiryar da wanda ya ga dama da falalarsa, ya kuma ɓatar da wanda ya ga dama da adalcinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya karanta tarihin duniya tun kafuwarta zuwa yau zai tabbatar da cewa, Allah bai yi wa ɗan’adam wata gagarumar ni’ima wadda ta kai aiko da manzanni ga mutane ba. Don haka babu waɗanda suka cika butulu kamar waɗanda suka bijire wa annabawa suka kuma ƙaryata su. Mafi girman ni’ima cikin

dangogin wannan ni'imar ita ce ni'imar aiko da Manzon Allah Muhammadu (ﷺ), don haka babu mafi munin butulci kamar kafirce masa da watsi da karantarwarsa.

2. A kowane zamani kuma a kowane wuri babu abin da azzalumai suke ganin mai haɗari a wurinsu kamar aƙidar kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka suke yin iya bakin ƙoƙarinsu su ga sun ɓatar da al'ummunsu, sun hana su fahimtar wannan aƙidar.

3. Mai hankali shi ne wanda ya fahimci cewa, jin daɗin duniya ɗan kaɗan ne kuma ba mai ɗorewa ba, don haka bai yarda ya shagaltar da shi ba har ya manta da neman jin daɗin lahira.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan ambaci salla tare da zakka yayin magana a kan lahira domin nuni ga cewa, ta hanyar kula da waɗannan ibadu biyu ne bawa zai sami tsira a lahira.

5. Duk wanda ya mutu yana kafiri ba zai sami ceto ba ranar alƙiyama.

Suratu Ibrahim (28-31)

*أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ بَدَّلُواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ كُفۡرٗا وَأَحَلُّواْ قَوۡمَهُمۡ دَارَ ٱلۡبَوَارِ ٢٨ جَهَنَّمَ يَصۡلَوۡنَهَاۖ وَبِئۡسَ ٱلۡقَرَارُ ٢٩ وَجَعَلُواْ لِلَّهِ أَندَادٗا لِّيُضِلُّواْ عَن سَبِيلِهِۦۗ قُلۡ تَمَتَّعُواْ فَإِنَّ مَصِيرَكُمۡ إِلَى ٱلنَّارِ ٣٠ قُل لِّعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ يُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُنفِقُواْ مِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ سِرّٗا وَعَلَانِيَةٗ مِّن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَ يَوۡمٞ لَّا بَيۡعٞ فِيهِ وَلَا خِلَٰلٌ ٣١

28. Shin ba ka ga waɗanda suka musanya ni'imar Allah da kafirci ba, suka kuma jefa mutanensu gidan hallaka?

29. (Watau) Jahannama, za su shige ta; makoma kuwa ta munana.

30. Sun sanya wa Allah abokan tarayya don su ɓatar (da mutane) daga hanyarsa. Ka ce: "Ku ji daɗi (kaɗan a duniya), to lalle makomarku wuta ce!"

31. Ka ce da bayina waɗanda suka yi imani, su tsayar da salla kuma su ciyar daga abin da Muka arzuta su da shi, a ɓoye da sarari tun kafin zuwan ranar da babu ciniki a cikinta, kuma babu abota.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tabbatar wa Annabi (ﷺ) abin da ya sani game da kafiran Ƙuraishawa na butulce wa ni'imar da Allah ya yi musu ya, ba su zaman lafiya a garuruwansu yayin da wasu garuruwan suke cikin tashin hankali da hargitsi, sannan ya yi musu wata babbar ni'ima wadda ta zarce kowace irin ni'ima da ya taɓa yi musu, watau shi ne ya aiko musu da Annabi daga cikin jinsinsu, to amma maimakon su gode wa Allah sai suka butulce masa ta hanyar kafirci da ƙaryata Manzonsa, da haka suka jefa mabiyansu cikin gidan halaka, watau gidan wutar Jahannama wadda za su shige ta su kuma ɗandani azabarta. Tir da wannan makoma.
Sannan Allah ya bayyana irin mummunan ɓatan da suka faɗa ciki, kuma suka yi sanadiyyar ɓatan sauran mabiyansu, ya bayyana cewa, sun riƙi gumaka abokan tarayya da Allah suna bauta musu ba Allah ba, sannan suna ɓatar da wasu ta hanyarsu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, su ji daɗi ɗan kaɗan na duniya da bin soye-soyen zukatansu da yaɗa ɓarna a bayan ƙasa, to amma su sani cewa, ƙarshen makomarsu ranar alƙiyama ita ce wutar Jahannama ba su da wata makoma ba wannan ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya umarci muminai su tsayar da sallolinsu cikakku kamar yadda aka umarce su, su kuma taimaka da dukiyoyinsu ga mabuƙata; taimako na wajibi, kamar zakka da makamanciyarta, ko na mustahabbi. Suna iya yin haka a ɓoye don gudun riya, suna kuma iya yin haka a bayyane don a yi koyi da su kafin ranar alƙiyama ta zo, ranar da dukiya ko abota ba za su amfani kowa ba, ba za a karɓi fansa daga wani ba domin kuɓutar da shi daga azaba, aboki ba zai iya ceton abokinsa ba sai da izinin Allah ga wanda ya yarda da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman matsayin ɗan'adam a wurin Allah don haka ya hore masa manya-manyan halittu domin amfaninsa.

2. Lissafa wasu daga cikin ni'imomin Allah ga ɗan'adam yana nuni ga cewa, wasu mutane suna butulce wa ni'imomin Allah masu ɗimbin yawa.

3. Ni'imomin Allah ga ɗan'adam ba sa lissafuwa duka ballantana ya iya bayar da haƙƙin godiya gare su gaba ɗaya, don haka yana da kyau matuƙa mumini ya zamanto bai gushe ba harshensa yana ɗanye shataf wajen ambaton Allah da gode masa.

4. Yana daga cikin ɗabi'ar ɗan'adam yawan zalunci da yawan butulci. Don haka babu abin da zai magance masa wannan ɗabi'a sai tsoron Allah da yawan godiya ga Allah bisa ga ni'imominsa.

Suratu Ibrahim (32-34)
ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلْفُلْكَ لِتَجْرِىَ فِى ٱلْبَحْرِ بِأَمْرِهِۦ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلْأَنْهَٰرَ ﴿٣٢﴾ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ دَآئِبَيْنِ ۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ ﴿٣٣﴾ وَءَاتَىٰكُم مِّن كُلِّ مَا سَأَلْتُمُوهُ ۚ وَإِن تَعُدُّوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ لَا تُحْصُوهَآ ۗ إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لَظَلُومٌ كَفَّارٌ ﴿٣٤﴾

32. Allah ne Wanda Ya halicci sammai da ƙasa, Ya kuma saukar da ruwa daga sama, sai Ya fitar da 'ya'yan itace don arzuta ku; Ya kuma hore muku jiragen ruwa don ku yi tafiya a cikin kogi da umarninsa, Ya kuma hore muku ƙoramu.

33. Ya kuma hore muku rana da wata tutur; Ya kuma hore muku dare da rana.

34. Ya kuma ba ku daga duk abin da kuka roƙe Shi. In da za ku ƙirga ni'imomin Allah to ba za ku iya ƙididdige su ba. Lalle mutum mai yawan zalunci ne mai yawan butulci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kaɗan daga cikin ɗimbin ni'imomi da ya yi wa ɗan'adam amma yake nuna butulcinsa, har ma yake ƙaryata annabawansa. Daga cikin waɗannan ni'imomi akwai halittar sammai da ƙasa wadda Allah ya yi ba tare da kwaikwayon kowa ba, ba kuma tare da wani ya taimaka masa ba, sannan ya saukar da ruwan sama wanda ya fitar da tsirrai da abinci da kayan marmari iri-iri da shi domin amfanin 'yan'adam, sannan kuma ya hore musu jiragen ruwa domin sufuri da ɗaukan kaya masu nauyi suna gudu a kan teku cikin ikon Allah. Bayan haka kuma ya samar musu da ƙoramu na ruwan sha, su sha su kuma shayar da dabbobinsu da shuke-shukensu.
Daga cikin waɗannan ni'imominsa kuma akwai halittar rana da wata waɗanda ya hore wa ɗan'adam amfani da haskensu da zafin rana, ga su suna gudana a sama ko da yaushe ba yankewa. Sannan kuma ya

hore musu dare da yini waɗanda suke bibiyar juna, ya sanya dare ya zama lokacin hutawa da barci, ya sanya yini ya zama lokacin kujuba-kujuba da neman abinci.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dunƙule waɗannan ni'imomi da cewa, ya ba wa 'yan'adam duk wani abu da suka roƙe shi na buƙatarsu da ma wanda ba su roƙe shi ba, domin idan da mutane za su lissafa ni'momin Allah a gare su, to ba za su iya ƙididdige su ba saboda yawansu. Waɗannan da aka ambata ma misalai ne aka bayar, to amma sau da yawa mutum yakan mance da waɗannan ni'imomin ya ƙi godiya ga Allah, ya ma butulce masa ya yi ta yin kafirci da saɓo iri-iri. Da ma wannan shi ne halin ɗan'adam idan bai samu tarbiyya ta annabawa ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Addu'ar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ga garin Makka tana nuna falalar wannan gari.

2. Kula da tsaro da zaman lafiyar ƙasa yana daga cikin muhimman abubuwan da mutane nagari suke fata da addu'ar wanzuwarsu. Duk matsayin bawa da darajarsa a wurin Allah wajibi ne ya jiye wa kansa da iyalansa tsoron faɗawa cikin shirka da Allah.

3. Yana daga cikin hanyoyin tarbiyya yi wa 'ya'ya addu'a da roƙa musu Allah ya tsare musu imaninsu da Tauhidinsu.

4. Alaƙar addini da aƙida tana gaba da alaƙa ta jini da dangantaka.

5. Masu saɓon Allah suna buƙatar addu'ar samun rahama da gafara daga Allah.

6. Babban matsayin salla domin ita ce wajibi na biyu bayan Tauhidi.

7. Haihuwa bayan mutum ya tsufa wata babbar ni'ima ce da ta cancanci bawa ya gode wa Allah a kanta.

8. Duk girman matsayin bawa a wurin Allah yana da buƙatar yawaita addu'a da roƙon Allah buƙatunsa na duniya da na lahira.

Suratu Ibrahim (35-41)
وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ رَبِّ ٱجْعَلْ هَٰذَا ٱلْبَلَدَ ءَامِنًا وَٱجْنُبْنِي وَبَنِيَّ أَن نَّعْبُدَ ٱلْأَصْنَامَ ﴿٣٥﴾ رَبِّ إِنَّهُنَّ أَضْلَلْنَ كَثِيرًا مِّنَ ٱلنَّاسِ ۖ فَمَن تَبِعَنِي فَإِنَّهُۥ مِنِّي ۖ وَمَنْ عَصَانِي فَإِنَّكَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٣٦﴾ رَّبَّنَآ إِنِّيٓ أَسْكَنتُ مِن ذُرِّيَّتِي بِوَادٍ غَيْرِ ذِي زَرْعٍ عِندَ بَيْتِكَ ٱلْمُحَرَّمِ رَبَّنَا لِيُقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ فَٱجْعَلْ أَفْـِٔدَةً مِّنَ ٱلنَّاسِ تَهْوِىٓ إِلَيْهِمْ وَٱرْزُقْهُم مِّنَ ٱلثَّمَرَٰتِ لَعَلَّهُمْ يَشْكُرُونَ ﴿٣٧﴾ رَبَّنَآ إِنَّكَ تَعْلَمُ مَا نُخْفِي وَمَا نُعْلِنُ ۗ وَمَا يَخْفَىٰ عَلَى ٱللَّهِ مِن شَىْءٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فِى ٱلسَّمَآءِ ﴿٣٨﴾ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى وَهَبَ لِى عَلَى ٱلْكِبَرِ إِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ ۚ إِنَّ رَبِّى لَسَمِيعُ ٱلدُّعَآءِ ﴿٣٩﴾ رَبِّ ٱجْعَلْنِي مُقِيمَ ٱلصَّلَوٰةِ وَمِن ذُرِّيَّتِى ۚ رَبَّنَا وَتَقَبَّلْ دُعَآءِ ﴿٤٠﴾ رَبَّنَا ٱغْفِرْ لِى وَلِوَٰلِدَىَّ وَلِلْمُؤْمِنِينَ يَوْمَ يَقُومُ ٱلْحِسَابُ ﴿٤١﴾

35. (Ka tuna) kuma lokacin da Ibrahimu ya ce: "Ya Ubangijina, Ka sanya wannan gari (Makka) ya zama amintacce, kuma Ka nesantar da ni da 'ya'yana daga bauta wa gumaka.

36. "Ya Ubangijina, lalle su (gumakan) sun ɓatar da mutane masu yawa; wanda kuwa ya bi ni to lalle shi yana tare da ni; wanda kuma ya saɓa mini to lalle Kai Mai gafara ne, Mai jin ƙai."

37. “Ya Ubangijinmu, lalle ni na zaunar da wasu daga zuriyata a wani kwari wanda ba a shuka a cikinsa kusa da Ɗakinka mai alfarma; ya Ubangijinmu don su tsai da salla, to Ka sanya zukatan mutane su riƙa karkatowa zuwa gare su, kuma Ka arzuta su da ‘ya’yan itace don su gode (maka).

38. “Ya Ubangijinmu, lalle Kai Ka san abin da muke ɓoyewa da abin da muke bayyanawa. Babu wani abu a cikin ƙasa ko a cikin sama da zai ɓuya ga Allah.

39. “Dukkan yabo ya tabbata ga Allah wanda Ya ba ni Isma’ila da Is’haƙa a cikin halin tsufa. Lalle Ubangijina tabbas Mai jin roƙo ne.

40. “Ya Ubangijina, Ka sanya ni in zama mai tsayar da salla da kuma zuriyata. Ya Ubangijinmu, Ka karɓi addu’ata.

41. “Ya Ubangijinmu Ka gafarta mini, ni da iyayena da kuma muminai ranar da hisabi zai kankama.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ɓangare na labarin Baban annabawa, Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da yadda ya yi kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai da ƙaurace wa bautar gumaka. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tuna lokacin da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ɗauko kuyangarsa Hajara tare da ɗanta Annabi Isma’ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kawo su kwarin Makka ya ajiye su ya tafi ya bar su da umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Ya ɗaga hannu ya yi musu addu’a da cewa, Allah ya mayar da wannan wuri ya zama gari mai aminci da zaman lafiya, ba za a zubar da jinin wani ko zaluntar wani a cikinsa ba. Ya kuma roƙe shi ya nesanta shi tare da ‘ya’yansa daga bautar gumaka.
Sannan ya ambaci abin da ya sa shi tsoron shi ko ‘ya’yansa wani ya faɗa cikin shirka, da cewa, su waɗannan gumaka sun ɓatar da mutane da dama domin sun ɗauki cewa, za su cece su a lahira, don haka suke bauta musu ba Allah ba. Ya tabbatar da cewa, duk wanda ya bi shi daga cikin mutane ya kaɗaita Allah da bauta, to ya tabbata cikin mabiyansa kuma cikin jama’arsa. Duk kuwa wanda ya saɓa masa ya rungumi bautar wanin Allah, ya ƙi yi wa Allah biyayya, to Allah shi mai gafara ne ga wanda ya ga dama ya gafarta masa, mai jin ƙai ne ga wanda ya nufe shi da jin ƙansa.
Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da faɗa wa Allah cewa, ya zaunar da wasu daga zurriyarsa, su ne ɗansa Isma’ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifiyarsa Hajara, sai kuma jikokinsa ‘ya’yan Isma’ilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya zaunar da su a wani kwari wanda ba a shuka a cikinsa, babu ko ruwan sha kusa da Ɗakin Ka’aba, watau garin Makka. Ya bayyana cewa, ya saukar da su ne a wannan wuri don su tsayar da salla, domin ita ce ginshiƙin addini bayan Kalmar Shahada, don haka duk wanda ya tsayar da ita ya kula da ita, to zai kula da sauran ibadunsa. Ya kuma roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karkato da zukatan mutane zuwa gare su, su riƙa marmarin ziyarar wannan gari koyaushe. Ya kuma arzuta su da kayan marmari iri-iri da za a riƙa shigo musu da su daga ko’ina a duniya, domin su gode wa Allah game da ni’imominsa da ya yi musu.
Sannan ya ƙara tabbatar da cikakken sanin Allah ga komai, ya san abin da mutane suke ɓoyewa da abin da suke bayyanawa; babu abin da yake ɓuya gare shi a sama yake ko a ƙasa. Haka kuma ya san duk irin buƙatar da Annabi Ibrahimu da zurriyyarsa suke da ita kuma zai taimaka musu ya biya musu ita.
Sai kuma ya yi yabo da godiya da kirari ga Allah wanda ya amsa masa addu’arsa ya yi masa baiwa da Isma’ila da Is’haƙa bayan ya tsufa tukuf har ya fitar da rai daga samun haihuwa. Lalle Allah mai amsa addu’ar duk wanda ya roƙe shi ne.
Daga nan sai Annabi Ibrahimu ya roƙi Allah ya sanya shi ya zama mai tsayar da salla da sharuɗɗanta yadda ya kamata, hakanan su ma zurriyyarsa su zamo masu kula da salla kamar yadda ya dace, yana mai fatan Allah ya karɓa masa addu’arsa.

Sai kuma ya yi wa mahaifansa addu'ar Allah ya gafarta musu, tare da sauran muminai maza da mata, ya yafe musu zunubbansu a ranar da za a tsayar da su a gabansa domin yi musu hisabi.
Da ma Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mahaifinsa alƙawarin nema masa gafara wurin Allah, kamar yadda ya zo a cikin [*Suratu Maryam*, aya ta 47], to shi ne a nan ya cika alƙawarinsa. Daga baya ne kuma Allah ya sanar da shi cewa, mahaifinsa ba zai yi imani ba, zai mutu a cikin kafirci, sai ya dakatar da yi masa addu'ar neman gafara, kamar yadda [aya ta 114 a cikin *Suratut Tauba*] ta bayyana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mummunan sakamakon zalunci.

2. Jinkirta wa azzalumi azaba ba ya nufin Allah ya ƙyale shi ko ya manta da shi.

3. Yayin da azzalumi yake yin zaluncinsa a nan duniya hankalinsa a kwance, to zai zo a ranar alƙiyama a firgice a tsorace saboda mummunan sakamakon da zai gani a ranar.

4. Sauran kufan wuraren al'ummun da Allah ya hallakar da su gabanin wannan al'umma, wurare ne na ɗaukar izina da wa'azi, ba wurare ne na yawon buɗe ido da shaƙatawa ba.

5. Zalunci zunubi ne da ke jawo Allah ya hallaka al'umma a dalilinsa.

6. Duk girman tanadin maƙiya Allah da makircinsu wani ƙanƙanin abu ne a wurin Allah babu inda zai je, Allah zai tarwatsa shi da ƙarfin ikonsa.

7. Lallashin muminai da kada su ɗaga hankalinsu game da girman makircin maƙiyansu da suke gani, su dogara ga Allah ya ishe su komai.

8. Taimakon Allah ga masoyansa tabbataccen al'amari ne, lokaci kawai yake jira, domin Allah ba ya saɓa wa manzanninsa da muminai alƙawarin da ya yi musu.

9. Ranar alƙiyama Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai sake zubin halittar sammai da ƙasa yayin da duk wani na kwance cikin ƙabarinsa zai fito da gangar jikinsa ɗauke da ayyukansa domin fuskantar hisabi.

10. Babbar manufar saukar da Alƙur'ani ga mutane ita ce isar musu da saƙon Allah wanda ya ƙunshi abubuwa kamar haka:
a) Yi musu gargaɗi da azabar Allah.
b) Sanar da su Allah shi ne kaɗai abin bauta ba tare da yi masa shirka ba.
c) Don masu hankali su wa'azantu da abin da ya ƙunsa.

Suratu Ibrahim (42-52)
وَلَا تَحۡسَبَنَّ ٱللَّهَ غَٰفِلًا عَمَّا يَعۡمَلُ ٱلظَّٰلِمُونَۚ إِنَّمَا يُؤَخِّرُهُمۡ لِيَوۡمٖ تَشۡخَصُ فِيهِ ٱلۡأَبۡصَٰرُ ٤٢ مُهۡطِعِينَ مُقۡنِعِي رُءُوسِهِمۡ لَا يَرۡتَدُّ إِلَيۡهِمۡ طَرۡفُهُمۡۖ
وَأَفۡـِٔدَتُهُمۡ هَوَآءٞ ٤٣ وَأَنذِرِ ٱلنَّاسَ يَوۡمَ يَأۡتِيهِمُ ٱلۡعَذَابُ فَيَقُولُ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ رَبَّنَآ أَخِّرۡنَآ إِلَىٰٓ أَجَلٖ قَرِيبٖ نُّجِبۡ دَعۡوَتَكَ وَنَتَّبِعِ ٱلرُّسُلَۗ أَوَ لَمۡ
تَكُونُوٓاْ أَقۡسَمۡتُم مِّن قَبۡلُ مَا لَكُم مِّن زَوَالٖ ٤٤ وَسَكَنتُمۡ فِي مَسَٰكِنِ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ وَتَبَيَّنَ لَكُمۡ كَيۡفَ فَعَلۡنَا بِهِمۡ وَضَرَبۡنَا لَكُمُ
ٱلۡأَمۡثَالَ ٤٥ وَقَدۡ مَكَرُواْ مَكۡرَهُمۡ وَعِندَ ٱللَّهِ مَكۡرُهُمۡ وَإِن كَانَ مَكۡرُهُمۡ لِتَزُولَ مِنۡهُ ٱلۡجِبَالُ ٤٦ فَلَا تَحۡسَبَنَّ ٱللَّهَ مُخۡلِفَ وَعۡدِهِۦ رُسُلَهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ

عَزِيزٌ ذُو ٱنتِقَامٍ ﴿٤٢﴾ يَوْمَ تُبَدَّلُ ٱلْأَرْضُ غَيْرَ ٱلْأَرْضِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ ۖ وَبَرَزُوا۟ لِلَّهِ ٱلْوَٰحِدِ ٱلْقَهَّارِ ﴿٤٣﴾ وَتَرَى ٱلْمُجْرِمِينَ يَوْمَئِذٍ مُّقَرَّنِينَ فِى ٱلْأَصْفَادِ ﴿٤٤﴾
سَرَابِيلُهُم مِّن قَطِرَانٍ وَتَغْشَىٰ وُجُوهَهُمُ ٱلنَّارُ ﴿٤٥﴾ لِيَجْزِىَ ٱللَّهُ كُلَّ نَفْسٍ مَّا كَسَبَتْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ﴿٤٦﴾ هَٰذَا بَلَٰغٌ لِّلنَّاسِ وَلِيُنذَرُوا۟
بِهِۦ وَلِيَعْلَمُوٓا۟ أَنَّمَا هُوَ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ وَلِيَذَّكَّرَ أُو۟لُوا۟ ٱلْأَلْبَٰبِ ﴿٤٧﴾

42. Kada ka yi tsammanin Allah ba Shi da masaniyar abin da azzalumai suke aikatawa. Yana dai saurara musu ne kawai zuwa ranar da idanuwa za su fito zuru-zuru.

43. Suna masu gaggawa masu ɗage da kawunansu sama ba sa ƙiftawa; zukatansu kuma fanko ne (don tsananin firgita).

44. Kuma ka gargaɗi mutane game da ranar da azaba za ta zo musu, sai waɗanda suka yi kafirci su ce: "Ya Ubangijinmu, Ka saurara mana zuwa ɗan lokaci ƙanƙani, za mu amsa kiranka kuma mu bi manzanni." (Sai a ce da su): "A da ba ku ne kuka yi rantsuwa ba cewa ba za ku gushe ba?

45. "Kuka kuma zauna a gidajen waɗanda suka zalunci kawunansu, kuma irin yadda Muka yi musu ya bayyana a gare ku, Muka kuma ba ku misalai!"

46. Haƙiƙa kuma sun shirya makircinsu, sakamakon makircinsu kuma yana wurin Allah, ko da kuwa duwatsu za su gushe don makircinsu.

47. To kada ka yi tsammanin Allah Mai saɓa wa manzanninsa alƙawarinsa ne. Lalle Allah Mabuwayi ne Ma'abocin uƙuba.

48. (Ka tuna) ranar da za a sake ƙasa ba (wannan) ƙasar ba, da kuma sammai (ba waɗannan samman ba. Halittu) kuma suka fito (daga cikin ƙasa) a gaban Allah Makaɗaici, Mai rinjaye.

49. Kuma za ka ga masu laifi a wannan ranar a ƙuƙumce cikin maruruwa.

50. Rigunansu na (tafasasshen) man *ƙaɗiran* ne, kuma wuta za ta lulluɓe fuskokinsu.

51. (An yi musu haka ne) don Allah Ya saka wa kowanne rai da gwargwadon abin da ya aikata. Lalle Allah Mai saurin hisabi ne.

52. Wannan (Alƙur'ani) saƙo ne ga mutane don kuma a gargaɗe su da shi, kuma su san cewa Shi Allah Ɗaya ne, don kuma ma'abota hankali su wa'azantu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, kada ya yi tsammanin wai don Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jinkirta sauko da azabarsa ga azzalumai ya sha'afa ne daga miyagun ayyukansu na ƙaryata Allah da Manzonsa da hana mutane karɓar gaskiya da sauran miyagun ayyukansu. A'a, Allah ya san duk waɗannan abubuwa da suke aikatawa, domin babu abin da yake ɓuya gare shi. Yana dai jinkirta musu ne kawai har zuwa ranar alƙiyama, ranar da idanuwa za su fito zuru-zuru saboda tsananin fargaba da tsoron abin da za su gani. Lokacin da mutane za su fito daga cikin ƙaburburansu suna gaggawa wajen amsa kiran mai kiran su. Duk kowa ya ɗaga kansa sama yana kallon sararin samaniya a cike da fargaba da tsoro, ba mai iya dawo da ganinsa ƙasa sai dai su ci gaba da zare idanuwansu sama domin tsananin razani da suke ciki. Zukatansu kuma sun zama fanko ba sa iya fahimtar komai don tsananin firgita.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tsoratar da alʾummarsa azabar ranar alƙiyama, ranar da mutanen da suka zalunci kansu da aikata kafirci da shirka da Allah da saɓon Allah za su riƙa roƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jinkirta musu azaba, ya ma mayar da su duniya ko da na ɗan lokaci ƙanƙani ne domin su sami wata dama su yi imani da shi su bi manzannin da ya aiko musu.
Sai a mayar musu da martani cikin zargi da cewa, ba su ne a duniya suka rantse a kan cewa, ba za su rabo da rayuwarsu ta duniya zuwa ta lahira ba, domin ba su yarda da akwai tashi bayan mutuwa ba? Har ila yau a faɗa musu cewa, ba su ne suka zauna a gidajen al'ummun da suka gabace su ba, waɗanda suka zalunci kawunansu da kafirci da ƙaryata annabawa kamar Adawa da Samudawa da sauransu, kuma sun ga irin yadda Allah ya hallaka su, kuma ya yi ta ba su misalai iri-iri don su waʾazantu su gyara halayensu amma hakan bai amfane su ba?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan azzalumai da suka zauni gidajen al'ummun da suka gabace su sun shirya makirce-makirce iri-iri na yadda za su ga ƙarshen gaskiya da masu kira zuwa gare ta. Daga cikinsu har da waɗanda suka shirya kashe Manzon Allah (ﷺ), amma Allah yana sane da duk ƙulle-ƙullensu na makirci, kuma makircinsu a wurinsa bai taka kara ya karya ba, domin kuwa ai ba zai iya gusar da duwatsu daga mahallansu ba, saɓanin shirin Allah wanda babu mai iya tunkarar sa komai ƙarfinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara kwantar wa da Manzonsa hankali ya tabbatar masa cewa, ba zai saɓa alƙawarin nasara da ya yi masa ba, domin bai taɓa saɓa wa manzanninsa alƙawarin da ya yi musu ba, domin shi mabuwayi ne babu abin da ya fi ƙarfinsa, kuma zai ɗaukaka masoyansa ya ba su izza, kuma shi maʾabocin sakayyar uƙuba ne ga maƙiyansa kuma maƙiyan manzanninsa.
Sai ya bayyana inda sakamakon wannan azabar zai faru, shi ne ranar alƙiyama, ranar da za a canja wannan ƙasar da wata ƙasar fara ƙal, sammai ma a canja su da wasu sammai daban. A lokacin duk mutane za su fito daga ƙaburburansu ɗauke da ayyukansu domin tsayuwa gaban Allah wanda shi kaɗai ne mai mulki da isa a wannan ranar.

An karɓo daga Sahlu ɗan Saʾad (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Za a tattara mutane a ranar alƙiyama a kan wata ƙasa fara ƙal kamar gurasar farin gari mai tsafta, babu wata alama ta wani ɗanʾadam a kanta." [Bukhari #6521 da Muslim #2790].

An karɓo daga Aʾisha (Allah ya ƙara masa yarda) ta ce: "Ni ce farkon wadda ta tambayi Manzon Allah (ﷺ) game da wannan ayar [aya ta 48] na ce: "Ina mutane suke a wannan ranar ya Manzon Allah?" Sai ya ce: "Suna kan siraɗi." [Muslim #2791].

Hakanan lokacin da wani Bayahude ya tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa,: "Ina mutane za su kasance ranar da za a canja wannan ƙasar da wata ƙasar, a kuma canja sammai su ma?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya amsa masa da cewa,: "Suna cikin wani duhu kafin a hau gadar siraɗi." [Muslim #315]. Daga Saubanu (Allah ya kara masa yarda).

Baihaƙi ya fassara hadisin Aʾisha (Allah ya ƙara masa yarda) da wannan hadisin, watau faɗar "Suna kan siraɗi" yana nufin suna cikin wani duhu kafin hawan siraɗi wanda za su tsallaka ta kansa. [Dubi, Ibn Hajar, *Fatʾhul Bari*, Juzuʾi na 11, shafi na 376].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin azabar da za a yi wa kafirai a wannan rana. Ya bayyana abubuwa uku da za a yi musu azaba da su:

Na farko: za a haɗa sashinsu da sashe a ɗaure a mari. Za a dubi masu kafirci da laifuka iri ɗaya a haɗa su a ɗaure wuri guda.

Na biyu: za a yi musu tufafi da man *ƙadîran*, wani baƙin mai ne kamar kwalta yana da saurin kamawa da wuta, ga shi kuma da ɗan karen wari. Idan an shafe jikinsu da wannan mai za su yi baƙi ƙirin, su riƙa wani mummunan wari, sannan wuta ta riƙa saurin cinye fatunsu ana canja musu wasu.
Na uku : wuta za ta riƙa lulluɓe fuskokinsu, su ƙone ƙurmus.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu haka ne don ya saka wa kowane rai da sakamakon irin aikinsa, wanda ya yi aiki mai kyau ya ga sakamako mai kyau, watau gidan Aljanna, wanda kuwa ya yi aiki mummuna ya ga mummunan sakamako, watau wutar Jahannama. Lalle Allah mai saurin yi wa mutane hisabi ne a kan ayyukansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rufe wannan Surar da bayyana manufar saukar da Alƙur'ani ga mutane, watau don ya zamanto isar da saƙo ne gare su, a kuma gargaɗe su da abin da ya ƙunsa na tsoratarwa da narkon azaba, don kuma su san cewa, Allah shi kaɗai ne abin bautarsu, don haka su bauta masa kada su haɗa shi da kowa wajen bauta, kuma don masu hankali su wa'azantu da abin da yake cikinsa na darussa daban-daban.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani littafi ne mai bayanin komai dalla-dalla.

2. Duk wani kafiri sai ya yi nadamar rashin musuluntarsa a lokacin mutuwarsa da kuma ranar alƙiyama. Don haka Musulmi ya yi wa Allah godiya bisa ga wannan babbar ni'imar ta Musulunci da yake ciki, yayin da yawancin mutane suka rasa ta.

3. Al'ada ce ta kafirai a kowane zamani shagaltuwa da rayuwar duniya da more jin daɗinta da fafutukar tara ta gami da dogon buri su manta akwai ranar lahira tana nan tafe. Don haka wajibi ne mumini ya saɓa musu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aje wa kowace al'umma da ta yi zalunci lokacin hallakar da ita, ba a rage mata shi kuma ba a ƙara mata.
5. Duk wani zunubi dole ne a ga tasirinsa ko da kuwa bayan wani lokaci ne matuƙar ba a tuba ba.



15 Suratul Hijr

-

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna "*Suratul Hijr*", saboda zuwan wannan kalma a cikin Surar a aya ta 80, inda aka ambaci "*As`habul Hijri*". Su ne mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). *'Al-Hijr*' ɗin kuma sunan wurin da suka rayu ne.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:

Sura ce *Makkiyya*. An ruwaito wasu sun ce, daga cikin ayoyinta akwai waɗanda ba a Makka aka saukar da su ba, su ne aya ta 87 da ta 90 zuwa 93, to amma wannan magana mai rauni ce.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta hamsin da huɗu (54) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratu Yusuf*', kafin '*Suratul An'am*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Wannan Sura tana da ayoyi tis'in da tara (99).

5. Babban Jigonta:
Bayanin halayen masu faɗa da gaskiya da dalilan da suke sa su su ƙaryata gaskiya, da kuma bayanin mummunar makomarsu duniya da lahira.

6. Daga Cikin Abubuwan Da ta Kunsa Akwai:
• Bayanin falalar Alƙur'ani da zamantowarsa shiriya ga mutane.
• Gargaɗin kafirai da su guji faɗawa cikin nadama idan har sun ƙi karɓar Musulunci.
• Bayanin cewa ba wani abu ne ya hana kafirai karɓar gaskiya ba illa dulmiyar da suka yi cikin bin sha'awa-sha'awan zukatansu, da yi musu gargaɗi da azabar Allah idan ba su ba da gaskiya ba.
• Rarrashin Manzon Allah (ﷺ) da kwantar masa da hankali saboda rashin imanin kafirai da yawan matsa masa lamba da suke yi a kan sai ya kawo musu wasu mu'ujizoji da suka buƙata daga wajensa. Da bayyana masa cewa wannan da ma can al'ada ce ta kafirai tun da daɗewa, kuma ko da an kawo musu ayoyin ba za su yi imani ba sam-sam.
• Tsayar musu da hujjoji ta hanyar manya-manyan halittu na Allah da ni'imominsa da ya yi wa bayinsa, da bayanin rayuwa bayan mutuwa da hujjar hakan.
• Bayanin halittar jinsin ɗan'adam da irin karramawar da Allah ya yi masa, da labarin yadda Shaiɗan ya kafirce wa Allah.
• Ambaton labarin Annabi Ibrahimu da Annabi Luɗu da mutanen Annabi Shu'aibu da na Annabi Salihu.
• Tabbatar da digadigan Manzon Allah (ﷺ) da umartar sa da ya jira nasara tana nan tafe, kuma ya yi afuwa ga masu cutar da shi, ya bar su da Allah, ya mai da hankalinsa a kan muminai, Allah ya ishe shi kariya daga abokan gabansa.

Suratul Hijr (1-5)

الٓرٓۚ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ وَقُرۡءَانٖ مُّبِينٖ ١ رُّبَمَا يَوَدُّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡ كَانُواْ مُسۡلِمِينَ ٢ ذَرۡهُمۡ يَأۡكُلُواْ وَيَتَمَتَّعُواْ وَيُلۡهِهِمُ ٱلۡأَمَلُۖ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ٣ وَمَآ أَهۡلَكۡنَا مِن قَرۡيَةٍ إِلَّا وَلَهَا كِتَابٞ مَّعۡلُومٞ ٤ مَّا تَسۡبِقُ مِنۡ أُمَّةٍ أَجَلَهَا وَمَا يَسۡتَخِرُونَ ٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ALIF LAM RA Waɗannan ayoyin Littafi ne, kuma abin karatu ne mabayyani.

2. Waɗanda suka kafirta za su riƙa burin ina ma da sun zama Musulmai.

3. Bar su su ci kuma su ji daɗi, buri kuma ya shagaltar da su ; sai dai ba da daɗewa ba za su sani.

4. Ba wata alƙarya da Muka hallakar face tana da wani sanannen lokaci (a wurin Allah).

5. Ba wata al'umma da za ta riga lokacin da aka iyakance mata ko su jinkirta bayansa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da wasu haruffa [Dubi tafsirinmu na *Suratul Baƙara* don ƙarin bayani game da waɗannan haruffa]. Allah ya bayyana cewa, waɗannan ayoyi masu girman daraja ayoyin littafi ne da ya saukar kuma abin karatu ne da yake bayyana Kaɗaitakar Allah da hukunce-hukuncen shari'a.
Sai kuma ya bayyana cewa, kafirai a ranar alƙiyama ko kuma lokacin mutuwa za su yi nadamar ina ma a ce sun kasance su ma Musulmi ne. Domin a lokacin za su gane gaskiyar abin da ake faɗa musu, to amma nadamarsu ba za ta amfane su da komai ba domin lokacinta ya riga ya wuce.
Sai kuma ya ja hankalin Manzon Allah (ﷺ) game da abin da kafirai suke yi masa na izgili da cin zarafi cewa, ya ƙyale su, su ci su sha su ji daɗin duniya kamar dabbobi, dogon buri ya shagaltar da su su ƙi yin imani da aiki nagari, amma ba da daɗewa ba za su gane kurensu, za su fahimci irin babbar hasarar da suka tafka ranar alƙiyama.
Sannan Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu dalilin jinkirta musu azaba da aka yi ba wani abu ne ya sa haka ba sai domin sunnar Allah ta gabata a baya cewa, babu wata alƙarya da ya hallaka sai bayan da lokacin da ya iyakance musu ya cika. Da lokacin kuwa yayi ba za a ƙara musu ko da sa'a ɗaya ba kamar yadda ba za a rage musu komai ba. Don haka babu wata al'umma da za ta riga lokacin da aka yanke mata, kuma idan lokacinta ya yi ba za a jinkirta mata ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin masu kira zuwa ga gaskiya bisa ga izgili da yake samunsu da baƙaƙen maganganu, domin suna da kyakkyawan abin koyi daga Manzon Allah (ﷺ) wanda aka sha yi masa irin haka amma ya yi haƙuri.

2. Yalwatacciyar rahamar Allah. Wasu daga cikin bayinsa suna neman ya sauko musu da azaba, amma shi kuma yana saukar musu da rahamarsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin tsare Alƙur'ani daga duk wata gurɓatawa. Wannan ya ƙunshi tsare haruffansa da ma'anoninsa. Tsare ma'anonin Alƙur'ani ya tabbata ne ta hanyar tsare sunnar Annabi (ﷺ) wadda ita ce a matsayin mai sharhin ma'anonin Alƙur'ani.

4. Sunnar Allah ta gudana tun farko a kan yi wa masu faɗar gaskiya izgili, don haka na ƙarshe sun yi gadon wannan mummunar ɗabi'a ne daga na farko, saboda haka sai mabiya gaskiya su yi haƙuri kamar yadda annabawa suka yi.

5. Mutane da yawa sukan iya haɗuwa su yi ƙarya a kan wata maslaha tasu ta bai ɗaya.

Suratul Hijr (6-15)

وَقَالُواْ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِى نُزِّلَ عَلَيْهِ ٱلذِّكْرُ إِنَّكَ لَمَجْنُونٌ ۝٦ لَّوْ مَا تَأْتِينَا بِٱلْمَلَـٰٓئِكَةِ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّـٰدِقِينَ ۝٧ مَا نُنَزِّلُ ٱلْمَلَـٰٓئِكَةَ إِلَّا بِٱلْحَقِّ وَمَا كَانُوٓاْ إِذًا مُّنظَرِينَ ۝٨ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا ٱلذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَـٰفِظُونَ ۝٩ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ فِى شِيَعِ ٱلْأَوَّلِينَ ۝١٠ وَمَا يَأْتِيهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ۝١١ كَذَٰلِكَ نَسْلُكُهُۥ فِى قُلُوبِ ٱلْمُجْرِمِينَ ۝١٢ لَا يُؤْمِنُونَ بِهِۦ وَقَدْ خَلَتْ سُنَّةُ ٱلْأَوَّلِينَ ۝١٣ وَلَوْ فَتَحْنَا عَلَيْهِم بَابًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فَظَلُّواْ فِيهِ يَعْرُجُونَ ۝١٤ لَقَالُوٓاْ إِنَّمَا سُكِّرَتْ أَبْصَـٰرُنَا بَلْ نَحْنُ قَوْمٌ مَّسْحُورُونَ ۝١٥

6. Suka kuma ce: "Ya kai wanda aka saukar wa da Alƙur'ani, lalle kai tabbas mahaukaci ne.

7. "Me zai hana ka zo mana da mala'iku idan kana daga cikin masu gaskiya?"

8. (Allah ya ce): "Ba ma saukar da mala'iku sai da gaskiya; inda kuwa haka ya faru, to ba za a saurara musu ba."

9. Lalle Mu Muka saukar da Alƙur'ani, lalle kuma tabbas Mu za Mu kiyaye shi.

10. Haƙiƙa kuma Mun aiko (manzanni) a gabaninka cikin al'ummun farko.

11. Ba kuwa wani manzo da zai zo musu sai sun zamanto suna yi masa izgili.

12. Kamar haka ne Muke shigar da shi cikin zukatan kafirai.

13. Ba za su yi imani da shi ba; haƙiƙa kuma hanyar (sakamakon) mutanen farko ta gabata (wato hallakarwa).

14. Idan da Mun buɗe musu ƙofar sama har suka dinga hawa ta cikinta.

15. Tabbas da sun ce: "Ai an yi mana rufa-ido ne kawai; a'a, kai mu dai mutane ne da aka sihirce."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana irin izgili da kafirai suka riƙa yi wa Annabi (ﷺ) suna kiran sa da cewa: "Ya kai wanda aka saukar wa da wa'azi", watau a riyawarsa ba don sun yarda da cewa Alƙur'ani saukakke ne ba daga Allah. Sun kira shi da wannan ne don su jefe shi da taɓin hankali, suna nufin wai yana aikata abubuwa na marasa hankali. Suka ma ce wai idan har da gaske Allah ne ya aiko shi me ya hana shi zuwa da mala'iku waɗanda za su riƙa ba da shaida a kan abin da yake faɗa? Ko kuma me ya hana ya nemi a hallaka su tun da sun ƙi yin imani da shi, suna kuma aikata kafirci?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa, shi ba ya sauko da mala'iku sai da hikimar da za ta sanya haka. Wato sai lokacin hallaka su ya zo, kuma su sani duk sa'adda mala'iku suka sauko to ta faru ta ƙare, babu sauran a jinkirta musu, za a gaggauto musu da azaba ne nan take.

Sannan Allah ya bayyana musu cewa, idan suna neman shaida ne a kan gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ), to Alƙur'ani ma ya ishe su shaida, domin shi ne ya saukar masa da shi, yana kuma ɗauke da duk abin da suke buƙatar sani na hukunce-hukunce da tsarin rayuwar ɗan'adam kuma shi ne mai tsare shi daga ƙari ko ragi ko jirkitawa.
Sai kuma ya tabbatar wa da Annabi (ﷺ) cewa, ba shi ne manzo na farko da aka taɓa ƙaryatawa ba; gabaninsa ma Allah ya aiko da manzanni da yawa zuwa ga al'ummu da dama, amma babu wani manzo da ya zo musu sai sun ƙaryata shi sun yi masa izgili, to don haka kamar yadda Allah ya shigar da ɗabi'ar ƙaryatawa cikin zukatan waɗancan al'ummu to hakan ya shigar da ita cikin zukatan mushirikan Ƙuraishawa, sai suka bijire suka yi taurin kai, don haka mu'amalarsu ga Annabi ta yi kama da mu'amalar kafiran farko ga annabawansu, domin Allah ya tabbatar masa da cewa, ba za su yi imani da wannan Alƙur'ani da ya saukar masa ba. Al'adar Allah ta riga ta gabata ta hallakar da masu ƙaryata manzannin Allah, don haka sai su shiga taitayinsu, su ɗauki izina daga 'yan baya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, rashin imanin kafirai da ƙaryatawarsu ga Manzo (ﷺ) ba wai don rashin ƙwaƙƙwarar hujja ba ne; taurin kai ne nasu kawai da ƙoƙarin hana mutane su bi gaskiya. Ya kuma tabbatar da cewa, da zai buɗe musu wata ƙofa a sama har su samu suna hawa ta cikinta su leƙo abin da mala'iku suke gudanarwa, to da ba za su yi imani ba, za su tubure ne su ce kawai an yi musu rufa-ido ne, don haka abin da suke gani tasirin tsafi ne amma ba gaskiya ne ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abu ne mai kyau ga bawa ya riƙa yin duba zuwa ga halittar sammai da abin da ke cikinsu na taurari da rana da wata, domin kafa hujja da shi a kan Kaɗaitakar mahaliccinsu da girman ikonsa.

2. Duk wani nau'in arziki a hannun Allah yake; yana ba wa wanda ya ga dama gwargwadon yadda ya ga dama.

3. Allah ya halicci ƙasa ya kuma shimfiɗa ta ta yadda rayuwar ɗan'adam za ta dace a kanta. Ya ɗaure ta da manyan duwatsu domin hana ta tangal-tangal da halittun da ke kan doronta. Ya sanya nau'i iri-iri na tsirrai da bishiyoyi, kowanne bisa gwargwadon da ya dace da hikimarsa da maslahar ɗan'adam.

4. Allah ya tsare sama da taurari masu jifa, don haka aljannu ba sa samun sakewa domin sato jin abin da mala'iku suke tattaunawa a kansa na al'amuran da suka shafi gudanar da rayuwar mutane a ƙasa.

5. Wannan ƙasar da muke a kai ita ce duniyar da Allah ya tanadar wa ɗan'adam abin da ba zai rayu ba sai da shi, watau iskar shaƙa da ruwan sha da tsirrai. Don haka neman wata sabuwar duniya don rayuwar ɗan'adam a cikinta wani ɓata lokaci ne.

6. Wanda ya yi imani da cewa, taskar arziki tana hannun Allah, to ba zai nemi wanin Allah ba ya arzuta shi, kuma zai dangana da gwargwadon abin da Allah ya yanka masa na arzuki domin shi ne ya fi sanin maslaharsa.

Suratul Hijr (16-25)

وَلَقَدۡ جَعَلۡنَا فِي ٱلسَّمَآءِ بُرُوجٗا وَزَيَّنَّٰهَا لِلنَّٰظِرِينَ ١٦ وَحَفِظۡنَٰهَا مِن كُلِّ شَيۡطَٰنٖ رَّجِيمٍ ١٧ إِلَّا مَنِ ٱسۡتَرَقَ ٱلسَّمۡعَ فَأَتۡبَعَهُۥ شِهَابٞ مُّبِينٞ ١٨
وَٱلۡأَرۡضَ مَدَدۡنَٰهَا وَأَلۡقَيۡنَا فِيهَا رَوَٰسِيَ وَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ شَيۡءٖ مَّوۡزُونٖ ١٩ وَجَعَلۡنَا لَكُمۡ فِيهَا مَعَٰيِشَ وَمَن لَّسۡتُمۡ لَهُۥ بِرَٰزِقِينَ ٢٠ وَإِن مِّن
شَيۡءٍ إِلَّا عِندَنَا خَزَآئِنُهُۥ وَمَا نُنَزِّلُهُۥٓ إِلَّا بِقَدَرٖ مَّعۡلُومٖ ٢١ وَأَرۡسَلۡنَا ٱلرِّيَٰحَ لَوَٰقِحَ فَأَنزَلۡنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَسۡقَيۡنَٰكُمُوهُ وَمَآ أَنتُمۡ لَهُۥ بِخَٰزِنِينَ ٢٢

وَإِنَّا لَنَحۡنُ نُحۡيِۦ وَنُمِيتُ وَنَحۡنُ ٱلۡوَٰرِثُونَ ٤٣ وَلَقَدۡ عَلِمۡنَا ٱلۡمُسۡتَقۡدِمِينَ مِنكُمۡ وَلَقَدۡ عَلِمۡنَا ٱلۡمُسۡتَـٔۡخِرِينَ ٤٤ وَإِنَّ رَبَّكَ هُوَ يَحۡشُرُهُمۡۚ إِنَّهُۥ حَكِيمٌ عَلِيمٞ ٤٥

16. Haƙiƙa kuma Mun sanya taurari a sama, Muka kuma ƙawata ta ga masu gani.

17. Kuma Muka kiyaye ta daga duk wani shaiɗani la'ananne.

18. Sai dai wanda ya yi satar sauraro, sannan sai tauraro mai harshen wuta ya biyo shi.

19. Ƙasa kuma Mun shimfiɗa ta Muka sanya manyan duwatsu a cikinta, Muka kuma tsiro da kowane abu a cikinta ƙayyadajje.

20. Muka kuma sanya muku kayan rayuwa a cikinta, da kuma wanda ba ku ne kuke arzuta shi ba (wato bayi da dabbobi).

21. Babu wani abu wanda taskokinsa ba a wurinmu suke ba, kuma ba ma saukar da shi sai daidai wani gwargwado sananne.

22. Muka kuma aiko da iska mai yin barbara (ga giza-gizai), sai Muka saukar da ruwa daga sama Muka shayar da ku da shi, ba kuma ku ne masu taskance shi ba.

23. Lalle kuma tabbas Mu Muke rayawa kuma Muke kashewa, Mu ne kuma Masu gaje (komai).

24. Haƙiƙa kuma Mun san marigaya daga cikinku kuma haƙiƙa Mun san masu biyowa baya.

25. Lalle Ubangijinka kuma Shi zai tattara su. Lalle shi Mai hikima ne, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilai masu tabbatar da gaskiyar abin da Manzo (ﷺ) ya zo da shi na Tauhidi da gaskiyar tashin alƙiyama waɗanda kafirai suke ƙaryata shi a kansu. Allah ya bayyana cewa, ya halicci taurari a sama masu girma waɗanda matafiya suke yin alama da su a tafiye-tafiyensu a kan tudu da ruwa. Kuma ya ƙawata su ga duk wanda zai ɗaga kai ya kalle su. Ya yi haka ne domin su zama dalili ne mai tabbatar da cikakkiyar Ƙudurar Allah. Kuma ya yi wa sama irin wannan nagartacciyar halitta ce domin ta samu cikakken tsaro daga duk wani shaiɗani la'ananne mai ƙoƙarin ya sato labari daga sama ; don haka duk wanda ya yi yunƙurin satar sauraro za a jefe shi da tauraro mai harshen wuta ya ƙona shi ko ya saka shi ya tagayyara.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, cikin dalilan cikar ikonsa akwai ƙasa wadda ya shimfiɗa ta mutane da dabbobi suna yawo a kanta, ya kuma kafa manya-manyan duwarwatsu a cikinta don kada ta riƙa tangal-tangal da su, sannan kuma ya fitar da tsirrai iri daban-daban daga cikinta gwargwadon yadda ya dace da buƙatunsu da kuma hikimarsa. Sannan kuma ya sanya kayan rayuwa a cikinta na abubuwan ci da na sha waɗanda duk wani abu mai rai yake da buƙata. Ya bayyana cewa, shi ne yake arzuta dabbobi da mutanen da ba su da mai ba su sai shi. A taƙaice dai babu wani abu da mutane ko dabbobi suke amfani da shi face Allah ne mai ikon samar da shi da hore musu amfani da shi, kuma yana samar da komai ne gwargwadon hikimarsa da kuma buƙatar masu buƙata.
Allah kuma ya ci gaba da bayyana cikakken ikonsa, da cewa, shi ne yake aiko iska wadda take yi wa girgije barbara sai ya cika da ruwa, Allah kuma ya saukar da ruwan sama daga gare shi a wuraren da ya ga dama, sai ya shayar da mutane da dabbobi da shuke-shuke da shi, kuma ya ajiye shi a cikin koguna da ƙoramu da maremari na ruwa da rijiyoyi, kuma babu wani mai iya yin wannan aikin sai Allah shi kaɗai.

Kuma daga cikin kamalar ikon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne yake rayawa yake kuma kashewa, yake tayar da halitta bayan mutuwa, shi kuma wanzajje ne, shi ne mai gaje ƙasa da duk abin da ke cikinta bayan duk wani mai rai ya mutu. Babu abin da bai sani ba; ya san waɗanda za a riga haihuwarsu su riga mutuwa, ya san kuma waɗanda za a haife su daga baya su mutu. Ya tabbatar wa Manzonsa cewa, zai tattara kowa da kowa a ranar alƙiyama domin yi musu hisabi, ya saka wa wanda ya kyautata aikinsa da kyakkyawan sakamako, ya kuma saka wa wanda ya yi mummunan aiki da mummunan sakamako. Shi Allah mai hikima ne cikin dukkan tsare-tsarensa, masanin komai ne babu abin da zai kuɓuce masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutum na farko da Allah ya halitta shi ne Annabi Adamu. Ya halicce shi daga yumɓu. Wannan shi ya ƙaryata masu cewa wai biri shi ne asalin ɗan'adam na farko. Yarda da wannan ra'ayin kuwa ƙaryata Alƙur'ani ne da littattafan annabawa gaba ɗaya.

2. Wuta ce asalin aljani na farko, watau Iblis.

3. Ɗan'adam halitta ne mai daraja a wurin Allah. Allah ya fifita ubanmu Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a kan mala'iku da aljannu, ya halicce shi da hannunsa ya kuma busa masa ruhinsa, sannan ya umarci mala'iku har da Iblis su yi masa sujjada, wanda hakan girmamawa ce ga jinsin ɗan'adam.

4. Iblis ya cancanci la'anar Allah ne saboda girman kansa da hassada da nuna alfahari da asalinsa a kan na Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Don haka duk wanda ya siffantu da waɗannan ɗabi'u to ya siffantu ne da ɗabi'un Shaiɗan.

5. Shaiɗan ba shi da ikon ɓatar da bayin Allah zaɓaɓɓu masu yin komai don Allah shi kaɗai ba don riya ba.

6. Wutar Jahannama tana da ƙofofi guda bakwai, kowace ƙofa akwai gungun masu laifin da za su shige ta.

Suratul Hijr (26-44)

وَلَقَدْ خَلَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ مِن صَلْصَٰلٍ مِّنْ حَمَإٍ مَّسْنُونٍ ﴿٢٦﴾ وَٱلْجَآنَّ خَلَقْنَٰهُ مِن قَبْلُ مِن نَّارِ ٱلسَّمُومِ ﴿٢٧﴾ وَإِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّى خَٰلِقٌۢ بَشَرًا
مِّن صَلْصَٰلٍ مِّنْ حَمَإٍ مَّسْنُونٍ ﴿٢٨﴾ فَإِذَا سَوَّيْتُهُۥ وَنَفَخْتُ فِيهِ مِن رُّوحِى فَقَعُوا۟ لَهُۥ سَٰجِدِينَ ﴿٢٩﴾ فَسَجَدَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ كُلُّهُمْ أَجْمَعُونَ ﴿٣٠﴾ إِلَّآ إِبْلِيسَ
أَبَىٰٓ أَن يَكُونَ مَعَ ٱلسَّٰجِدِينَ ﴿٣١﴾ قَالَ يَٰٓإِبْلِيسُ مَا لَكَ أَلَّا تَكُونَ مَعَ ٱلسَّٰجِدِينَ ﴿٣٢﴾ قَالَ لَمْ أَكُن لِّأَسْجُدَ لِبَشَرٍ خَلَقْتَهُۥ مِن صَلْصَٰلٍ
مِّنْ حَمَإٍ مَّسْنُونٍ ﴿٣٣﴾ قَالَ فَٱخْرُجْ مِنْهَا فَإِنَّكَ رَجِيمٌ ﴿٣٤﴾ وَإِنَّ عَلَيْكَ ٱللَّعْنَةَ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلدِّينِ ﴿٣٥﴾ قَالَ رَبِّ فَأَنظِرْنِىٓ إِلَىٰ يَوْمِ يُبْعَثُونَ ﴿٣٦﴾ قَالَ فَإِنَّكَ
مِنَ ٱلْمُنظَرِينَ ﴿٣٧﴾ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْوَقْتِ ٱلْمَعْلُومِ ﴿٣٨﴾ قَالَ رَبِّ بِمَآ أَغْوَيْتَنِى لَأُزَيِّنَنَّ لَهُمْ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَأُغْوِيَنَّهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٣٩﴾ إِلَّا عِبَادَكَ مِنْهُمُ
ٱلْمُخْلَصِينَ ﴿٤٠﴾ قَالَ هَٰذَا صِرَٰطٌ عَلَىَّ مُسْتَقِيمٌ ﴿٤١﴾ إِنَّ عِبَادِى لَيْسَ لَكَ عَلَيْهِمْ سُلْطَٰنٌ إِلَّا مَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلْغَاوِينَ ﴿٤٢﴾ وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمَوْعِدُهُمْ
أَجْمَعِينَ ﴿٤٣﴾ لَهَا سَبْعَةُ أَبْوَٰبٍ لِّكُلِّ بَابٍ مِّنْهُمْ جُزْءٌ مَّقْسُومٌ ﴿٤٤﴾

26. Kuma haƙiƙa Mun halicci mutum daga busasshen taɓo mai amo na wani yumɓu mai wari.

27. Aljani kuwa Mun halicce shi ne gabanin (halittar mutum) daga wuta mai tsananin zafi.

28. Kuma (ka tuna) lokacin da Ubangijinka ya ce da mala'iku: "Lalle Ni zan halicci mutum daga busasshen taɓo mai amo na wani yumɓu mai wari.

29. “To idan Na daidaita shi Na kuma busa masa daga ruhina, to ku faɗi kuna masu sujjada a gare shi.”

30. Sai mala’iku dukkaninsu suka yi sujjada gaba ɗaya.

31. Sai Iblis ya ƙi ya kasance tare da masu yin sujjadar.

32. (Allah) Ya ce: “Ya Iblis, me ka taka da ba za ka kasance tare da masu sujjada ba?”

33. (Iblis) ya ce: “Ba zai yiwu ba ni in yi sujjada ga wani mutum wanda Ka halitta daga busasshen taƃo mai amo na wani yumƃu mai wari.”

34. (Allah) Ya ce: “To ka fita daga cikinta (Aljannar), lalle kai korarre ne (daga rahamar Allah).

35. “Lalle kuma la’ana ta tabbata a kanka har zuwa ranar alƙiyama.”

36. (Iblis) ya ce: “Ya Ubangijina Ka surara min har zuwa ranar da za a tashe su (watau matattu).”

37. (Allah) Ya ce: “To lalle kana daga cikin waɗanda za a saurar musu.

38. “Har zuwa rana mai sanannen lokaci.”

39. (Iblis) ya ce: “Ubangijina, saboda ƃatar da ni da Ka yi, to lalle kuwa zan ƙawata musu (ƃarna) a bayan ƙasa, kuma tabbas zan ƃatar da su baki ɗaya.

40. “Sai fa bayinka zaƃaƃƃu daga cikinsu.”

41. (Allah) Ya ce: “Wannan hanya ce madaidaiciya, mai kaiwa gare Ni.

42. “Lalle bayina ba ka da wani iko a kansu, sai dai wanda ya bi ka daga ƃatattu.

43. “Lalle kuma Jahannama tabbas makomarsu ce baki ɗaya.

44. “Tana da ƙofofi bakwai, kowacce ƙofa tana da wani kaso (na kafirai) sananne (da za su shiga ta nan).”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin halittar ɗan’adam na farko, watau Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da yadda Iblis ya nuna ƙiyayyarsa da hassadarsa gare shi a gaban mahaliccinsa Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga busasshen taƃo mai amo kuma mai wari saboda daɗewa a ajiye. Ya kuma halicci uban aljannu tun kafin halittar Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi kuma daga wuta mai tsananin zafi.

An karƃo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “An halicci mala’iku daga haske, an kuma halicci aljannu daga harshen wuta, an kuma halicci Adamu daga abin da aka sifanta muku.” [Muslim #2996].Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya tuna lokacin da Allah ya faɗa wa mala’iku cewa, zai halicci Annabi Adamu daga busasshen yumƃu mai amo, ya kuma umarce su da idan ya gama daidaita halittarsa, to su faɗi gabansa su yi masa sujjada. Sai kuwa suka cika umarnin Allah dukkansu suka faɗi suka yi masa sujjada bayan Allah ya gama halittarsa ya busa masa rai. Iblis wanda yake

tare da mala'iku a lokacin ne kaɗai ya ƙi bin wannan umarni don girman kai da hassada. Da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye shi dalilinsa na ƙin yi wa Adamu sujjada bayan ya yi umarni da haka, sai ya amsa cikin nuna girman kai da cewa, ai sam shi bai dace da shi ya yi wa Adamu sujjada ba, saboda an halicce shi da busasshen taɓo mai amo da wari shi kuma an halicce shi da wuta.
Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Iblis da ya fita daga gidan Aljanna, kuma ya kore shi daga rahamarsa har abada, ya kuma la'ance shi har alƙiyama ta tashi.
Sai Iblis ya roƙi Allah da ya saurara masa kada ya karɓi ransa har zuwa lokacin tashin alƙiyama. Allah kuma ya karɓi roƙonsa ya ce ya saurara masa har lokacin tashin alƙiyama, lokacin da kowa zai mutu ya koma ga Allah, watau lokacin busar ƙaho ta farko. Sai Iblis ya yi alƙawari a gaban Allah, da cewa, tun da har ya ɓatar da shi to sai shi kuma ya ƙawata wa bayinsa hanyoyin saɓonsa a duniya, sai kuma ya ɓatar da su gaba ɗaya daga tafarki madaidaici, amma sai ya togace zaɓaɓɓun bayin Allah masu imani da ikhlasi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa da cewa, zaɓaɓɓun bayinsa kam ba shi da wani iko a kansu ballantana ya yi nasarar ɓatar da su, sai dai kawai ya ɓatar da ɓatattun mutanen da suka bi hanyarsa. Ya kuma tabbatar musu da cewa, Jahannama ce makomarsu gaba ɗayansu daga shi har su. Sannan Allah ya bayyana wannan wuta ta Jahannama da cewa, tana da ƙofofin shigarta har bakwai, kuma kowace ƙofa da akwai wani yanki na mabiya Iblis da za su shiga ta nan.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Taƙawa, watau kiyaye dokokin Allah, sababi ne na shiga Aljanna.

2. Mala'iku za su yi wa 'yan Aljanna kyakkyawar tarya da girmamawa.

3. 'Yan Aljanna za su riƙa ziyartar junansu a gidan Aljanna, su riƙa zama tare suna hira.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai cire duk wata ƙiyayya da gaba da ke tsakanin muminai kafin shigarsu Aljanna.

Suratul Hijr (45-48)
إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٍ ۝٤٥ ٱدۡخُلُوهَا بِسَلَٰمٍ ءَامِنِينَ ۝٤٦ وَنَزَعۡنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنۡ غِلٍّ إِخۡوَٰنًا عَلَىٰ سُرُرٖ مُّتَقَٰبِلِينَ ۝٤٧ لَا يَمَسُّهُمۡ فِيهَا نَصَبٞ وَمَا هُم مِّنۡهَا بِمُخۡرَجِينَ ۝٤٨

45. Lalle masu kiyaye dokokin Allah suna cikin gidajen Aljanna da idanuwan (ruwa).

46. (A ce da su): "Ku shige ta lafiya lau kuna amintattu."

47. Muka kuma cire abin da ke cikin zukatansu na ƙullata (suka zama) 'yan'uwa a kan gadaje suna fuskantar juna.

48. Wata gajiya ba za ta shafe su ba, kuma su ba waɗanda za a fitar ba ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka kiyaye dokokinsa suka guje wa hanyoyin Iblis. Sakamakon shi ne gidajen Aljanna waɗanda suke da idanuwan ruwa masu gudana. Yayin da suka zo shiga gidajensu na Aljanna kuma mala'iku za su riƙa faɗa musu su shiga gidajensu cikin aminci, ba tare da tsoron mutuwa ko rashin lafiya ko wani abin baƙin ciki ba. Allah kuma ya cire duk wata ƙiyayya da ƙullata da take cikin zukatansu, sun zama 'yan'uwa masu ƙaunar juna. Za su zazzauna a

kan kujeru suna fuskantar juna suna hira suna nishaɗi. Ba za su sha wata wahala a cikinta ba, kuma ba za a fito da su daga cikinta ba; za su yi ta zama ne a cikinta har abada.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Muminai za su kuɓuta daga shiga wuta, sai a tsayar da su a kan wata gada da take tsakanin Aljanna da wuta, a karɓar wa sashinsu haƙƙinsa daga sashi, watau zaluncin da suka yi wa juna a duniya, har sai an gama tsarkake su sai a yi musu izinin shiga Aljanna." [Bukhari #2440].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mala'ika Jibrilu ya zo wurin Annabi (ﷺ) ya ce: "Ya Manzon Allah, ga Khadija nan ta zo maka da ƙwaryar miya a cikinta ko kuma abinci ko abin sha, to idan ta zo gare ka ka isar mata da gaisuwa daga Ubangijinta, ka kuma yi mata albishir da wani gida a Aljanna na dutsen lu'u-lu'u, babu wata hayaniya ko wahala a cikinsa." [Bukhari #3820 da Muslim #2432].

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri da Abu Huraira, daga Annabi (ﷺ) ya ce: "Mai shela zai yi shelar cewa,: 'Ya ku 'yan Aljanna, za ku rayu lafiya lau ba za ku yi rashin lafiya ba har abada; kuma za ku rayu har abada ba za ku mutu, za ku ci gaba da zama da ƙuruciya ba za ku tsufa ba har abada; za ku ci gaba da jin daɗi ba za ku wahala ba har abada.'" [Muslim #2837].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rahamar Allah ta rinjayi azabarsa.

2. Wajibi ne mumini ya riƙa halarto da siffofin nan na Allah guda biyu tare, watau shi mai gafara ne kuma azabarsa mai tsanani ce, kada ya dage a kan saɓon Allah domin yana tsammanin samun rahama, kada kuma ya fitar da ƙauna daga samun rahamarsa saboda ya yi laifi, sai wannan ya hana shi tuba zuwa ga Allah.

3. Yana daga cikin ladabin shiga gidan mutane farawa da yi musu sallama don neman izinin shiga.

4. Yana daga cikin haƙƙin mumini amsa masa sallamarsa. An fi son amsa sallama kuma ta fi sallamar kyau.

5. Wajabcin girmama baƙo.

6. Annabawa sukan ji tsoron abin da a ɗabi'ance yakan iya ba wa duk wani ɗan'adam tsoro.

7. Yi wa mutum albishir da wani alheri da zai same shi tun gabanin ya same shi don ya faranta masa rai.

8. Haramcin fitar da ƙauna daga samun rahamar Allah.

9. Halaccin tambayar baƙo labarinsa.

10. Kusanci ga wani annabi ko wani salihi kaɗai ba zai sanya mutum samun tsira daga azabar Allah ba har sai ya yi imani ya kyautata aikinsa.

11. Muhimmancin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kulawar Allah gare shi saboda kasancewar Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cikin mabiyansa kuma farkon wanda ya yi imani da shi har ya zama kamar almajirinsa. Saboda haka lokacin da Allah ya yi nufin hallaka mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai ya umarci mala'iku da su fara biyawa ta wajen Annabi

Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) su yi masa albishir da samun haihuwa, sannan su gamsar da shi a kan abin da aka aiko su su yi na hallaka mutanen Annabi Luḍu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Bayan ya gamsu sai suka wuce wurin Annabi Luḍu don zartar da aikinsu.

Suratul Hijr (49-60)

*نَبِّئْ عِبَادِيٓ أَنِّيٓ أَنَا ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٤٩﴾ وَأَنَّ عَذَابِي هُوَ ٱلْعَذَابُ ٱلْأَلِيمُ ﴿٥٠﴾ وَنَبِّئْهُمْ عَن ضَيْفِ إِبْرَٰهِيمَ ﴿٥١﴾ إِذْ دَخَلُوا۟ عَلَيْهِ فَقَالُوا۟ سَلَٰمًا قَالَ إِنَّا مِنكُمْ وَجِلُونَ ﴿٥٢﴾ قَالُوا۟ لَا تَوْجَلْ إِنَّا نُبَشِّرُكَ بِغُلَٰمٍ عَلِيمٍ ﴿٥٣﴾ قَالَ أَبَشَّرْتُمُونِي عَلَىٰٓ أَن مَّسَّنِيَ ٱلْكِبَرُ فَبِمَ تُبَشِّرُونَ ﴿٥٤﴾ قَالُوا۟ بَشَّرْنَٰكَ بِٱلْحَقِّ فَلَا تَكُن مِّنَ ٱلْقَٰنِطِينَ ﴿٥٥﴾ قَالَ وَمَن يَقْنَطُ مِن رَّحْمَةِ رَبِّهِۦٓ إِلَّا ٱلضَّآلُّونَ ﴿٥٦﴾ قَالَ فَمَا خَطْبُكُمْ أَيُّهَا ٱلْمُرْسَلُونَ ﴿٥٧﴾ قَالُوٓا۟ إِنَّآ أُرْسِلْنَآ إِلَىٰ قَوْمٍ مُّجْرِمِينَ ﴿٥٨﴾ إِلَّآ ءَالَ لُوطٍ إِنَّا لَمُنَجُّوهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٥٩﴾ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ قَدَّرْنَآ إِنَّهَا لَمِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿٦٠﴾

49. Ka bai wa bayina labarin cewa lalle Ni, Ni ne Mai gafara, Mai jin ƙai.

50. Kuma lalle azabata ita ce azaba mai raɗaɗi.

51. Kuma ka ba su labari game da baƙin Ibrahimu.

52. Lokacin da suka shiga wurinsa suka ce: “Muna yi maka sallama”, ya ce: “Lalle mu a tsorace muke da ku.”

53. Suka ce: “Kada ka ji tsoro, lalle mu muna yi maka albishir ne da (samun) yaro mai ilimi.”

54. Ya ce: “Yanzu kwa yi mini albishir bayan kuwa ga shi tsufa ya kama ni? To da me kuma za ku yi min albishir?!”

55. Suka ce: “Mun yi maka albishir da gaskiya ne, don haka kada ka zamo daga masu ɗebe ƙauna.”

56. Ya ce: “Ba wanda zai ɗebe ƙauna daga rahamar Ubangijinsa, sai ɓatattun (mutane).”

57. Ya ce: “Me yake tafe da ku ya ku waɗannan manzanni?”

58. Suka ce: “Lalle mu an aike mu ne zuwa ga wasu mutane masu laifi (wato mutanen Luḍu).

59. “In ban da iyalin Luḍu, lalle tabbas za mu tserar da su baki ɗaya.

60. “Sai fa matarsa ita kam mun ƙaddara cewa tabbas za ta zama cikin halakakku.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya sanar da bayinsa cewa, shi mai gafara ne ga duk wanda ya yi laifi ya tuba ya nemi gafara. Kuma azabarsa mai raɗaɗi ce ga duk wanda zai yi laifi ya ƙi tuba zuwa gare shi. Don haka su tuba don su samu gafararsa su kuma kuɓuta daga azabarsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartarsa da ya ba su labarin baƙin mala’iku masu daraja da suka ziyarci Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka yi masa albishir da samun haihuwar ɗa da kuma hallaka mutanen Annabi Luḍu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Da suka shiga gare shi suka yi masa sallama shi kuma ya amsa musu da mafi kyan abin da suka yi masa sallama da shi. Ya tashi da gaggawa ya kawo musu soyayyen naman ɗan maraƙi domin su ci, saboda ya zaci cewa, mutane ne kamarsa. To amma sai ya kula sun ƙi cin wannan naman, sai ya tsorata da su ya faɗa musu cewa, shi fa

ya tsorata da lamarinsu. To amma sai suka kwantar masa da hankali da cewa su malaʾikun Allah ne, sannan suka yi masa albishir da samun haihuwar ɗa namiji wanda zai zama mai ilimi sosai. Jin wannan albishir nasu ya jefa Annabi Ibrahimu cikin mamaki, ya tambaye su, yanzu sa yi masa albishir irin wannan bayan ga shi tsufa ya kama shi, to wane irin albishir ne wannan suke yi masa?!
Sai malaʾiku suka amsa masa da cewa, sun yi masa albishir ne da gaskiya, don haka ya daina kokwanto, kuma kada ya cire tsammanin samun haihuwa saboda tsufansa. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna musu cewa, shi bai cire tsammanin samun rahamar Ubangijinsa ba, domin babu mai cire tsammani daga samun rahamar Allah sai ɓatattun mutane da suka saki hanyar Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, bayan hankalin Annabi Ibrahimu ya kwanta ya daina jin tsoro, sai ya shiga tambayar malaʾiku labarinsu da dalilin zuwansu. Sai suka faɗa masa cewa, an aiko su ne su hallaka wasu miyagun mutane masu ɓarna, watau mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka yi ƙaurin suna wajen neman maza maimakon su riƙa auren ‘yaʾya mata. Malaʾikun suka faɗa masa cewa, ai za su tserar da iyalan Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga hallakarwa in ban da matarsa ita kam za ta kasance cikin halakakku, domin ya tabbata ita kafira ce ba ta yi imani da Annabi Luɗu ba, kuma tana taimaka wa musu ɓarna wajen gudanar da ɓarnarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin tambayar baƙo domin sanin shi wane ne.

2. An hana su waiwaye ne don gudun kada tausayi ya kama su yayin da za su ga yadda ake hallakar da waɗannan mutane.

Suratul Hijr (61-66)
فَلَمَّا جَآءَ ءَالَ لُوطٍ ٱلۡمُرۡسَلُونَ ٦١ قَالَ إِنَّكُمۡ قَوۡمٞ مُّنكَرُونَ ٦٢ قَالُواْ بَلۡ جِئۡنَٰكَ بِمَا كَانُواْ فِيهِ يَمۡتَرُونَ ٦٣ وَأَتَيۡنَٰكَ بِٱلۡحَقِّ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ٦٤
فَأَسۡرِ بِأَهۡلِكَ بِقِطۡعٖ مِّنَ ٱلَّيۡلِ وَٱتَّبِعۡ أَدۡبَٰرَهُمۡ وَلَا يَلۡتَفِتۡ مِنكُمۡ أَحَدٞ وَٱمۡضُواْ حَيۡثُ تُؤۡمَرُونَ ٦٥ وَقَضَيۡنَآ إِلَيۡهِ ذَٰلِكَ ٱلۡأَمۡرَ أَنَّ دَابِرَ هَٰٓؤُلَآءِ مَقۡطُوعٞ مُّصۡبِحِينَ ٦٦

61. To lokacin da manzannin suka zo wa iyalin Luɗu.

62. Ya ce: “Lalle ku wasu mutane ne da ba a san su ba.”

63. Suka ce: “A’a, mu mun zo maka ne da abin da (mutanenka) suke kokwanto game da shi.

64. “Mun kuma zo maka da dahir, lalle kuma tabbas mu masu gaskiya ne.

65. “Sai ka tafi da iyalinka cikin wani yankin dare ka kuma riƙa bin su a baya, kada kuwa ɗaya daga cikinku ya waiwaya, kuma ku tafi inda aka umarce ku.”

66. Muka kuwa sanar da shi abin da Muka ƙaddara na wannan alʾamari cewa, ƙarshen waɗannan zai yanke ne da asuba.
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana labarta mana cewa, lokacin da malaʾikun suka bar wajen Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka iso wajen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cikin kamannin mutane, suka yi masa sallama ya amsa musu, sai ya bayyana musu cewa, bai gane ko su wane ne su ba. Da suka ga alamar ya tsorata da su sai suka kwantar masa da hankali da cewa, sun zo ne da niyyar hallaka mutanensa waɗanda suke shakkar aukuwar azaba a kansu, duk kuwa

da mummunan laifin da suke tafkawa na neman maza da lalata. Saboda haka mala'ikun suka tabbatar wa Annabi Luɗu cewa, da gaske suke ba da maganar wasa suka zo ba. Sai suka umarce shi da ya kwashe iyalansa cikin dare ya fita daga wannan garin ya bi su a baya, kuma kada wani daga cikinsu ya waiwaya komai suka ji yana faruwa, kawai su yi ta tafiya inda Allah ya umarce su su tafi.
Kuma Allah ya sanar da Annabi Luɗu ta hanyar wahayi cewa, ƙarshen mutanensa ya zo, domin da asuba Allah zai hallaka su ƙwansu da ƙwarƙwatarsu, har da matarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dagewar mutanen Annabi Luɗu a kan sai sun aikata mummunan laifin da suka saba da baƙinsa alama ce da take nuna zukatansu sun gama lalacewa,.

2. Don kada tausayi ya kama zuciyar Annabi Luɗu yayin da za a zo hallaka mutanensa Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara faruwar wasu abubuwa a gabansa waɗanda za su fusata shi sosai ya ƙara tsanar su saboda tsananin zaƙewarsu cikin ɓarna har ya yi fatan halakarsu shi da kansa.

3. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi nufin hallaka wata al'umma sai sharrinsu da ta'addancinsu ya yi ta ƙaruwa, har idan ya kai maƙura Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aukar musu da azabar da ta cancance su.

4. Gargaɗi da wa'azantarwa ta hanyar bayar da labarin al'ummun da Allah ya hallaka.

5. Kufan gidaje da matsugunan waɗanda aka yi wa azaba wurare ne na ɗaukar izina da wa'azi, ba wurare ne na buɗe ido da shaƙatawa ba.

Suratul Hijr (67-77)
وَجَآءَ أَهۡلُ ٱلۡمَدِينَةِ يَسۡتَبۡشِرُونَ ٦٧ قَالَ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ ضَيۡفِي فَلَا تَفۡضَحُونِ ٦٨ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُخۡزُونِ ٦٩ قَالُوٓاْ أَوَ لَمۡ نَنۡهَكَ عَنِ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٧٠
قَالَ هَٰٓؤُلَآءِ بَنَاتِيٓ إِن كُنتُمۡ فَٰعِلِينَ ٧١ لَعَمۡرُكَ إِنَّهُمۡ لَفِي سَكۡرَتِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ٧٢ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلصَّيۡحَةُ مُشۡرِقِينَ ٧٣ فَجَعَلۡنَا عَٰلِيَهَا سَافِلَهَا وَأَمۡطَرۡنَا
عَلَيۡهِمۡ حِجَارَةٗ مِّن سِجِّيلٍ ٧٤ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّلۡمُتَوَسِّمِينَ ٧٥ وَإِنَّهَا لَبِسَبِيلٖ مُّقِيمٍ ٧٦ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ ٧٧

67. Mutanen garin kuma suka zo suna murna (da ganin baƙin).

68. Ya ce: "Lalle waɗannan baƙina ne, kada fa ku kunyata ni.

69. "Kuma ku kiyaye dokokin Allah, kada ku tozarta ni."

70. Suka ce: "Ashe ba mu hana ka (ka saukar da) mutane (baƙi ba)?"

71. Ya ce: "Ga 'ya'yana nan (ku aura) idan kun kasance masu aikata (haka).

72. "Na rantse da rayuwarka lalle su tabbas suna cikin mayensu suna ta ɗimuwa."

73. Sai tsawa ta auka musu lokacin hudowar rana.

74. Sai Muka mayar da samanta ya koma ƙasa, Muka kuma yi musu ruwan duwatsu soyayyu.

75. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga masu hangen nesa.

76. Lalle kuma ita (alƙaryar) tabbas tana kan wani gwadabe ne miƙaƙƙe.

77. Lalle a game da wannan tabbas akwai izina ga muminai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana cewa, lokacin da mutanen alƙaryar Sadum suka sami labarin saukar wasu baƙin samari a gidan Annabi Luɗu sai suka yiwo dafifi suka zo suna murnar sun sami abin da suke nema. Da Annabi Luɗu ya gan su sai ya tare su yana roƙonsu da cewa, waɗannan mutanen fa baƙinsa ce, su ji tsoron Allah kada su kunyata shi a gaban baƙinsa. Yana yi musu magiya su ji tsoron Allah su guji aikata wannan mummunan aiki nasu, kada su tozarta shi.
Annabi Luɗu ya yi wannan magana ne kafin ya san cewa waɗannan baƙi nasa mala'ikun Allah ne, kamar yadda yake a [*Suratu Hud*, aya ta 78-80].
Duk da wannan magiya ta Annabi Luɗu gwiwar mutanensa ba ta yi sanyi ba, sai suka amsa masa da cewa, ashe ba sun yi masa kashedi a kan karɓar baƙuntar mutane ba? Watau shi ne ya jawo wa kansa abin kunya.
Sai Annabi Luɗu ya nuna musu `ya`yansu mata da Allah ya halitta musu don su yi auratayya a tsakaninsu, ya umarce su cewa, su je mana su aure su. To amma ina, idonsu ya rufe sun gigice ba su san irin mummunan sakamakon da wannan rashin kunyar zai haifar musu ba, shi ya sa Allah ya yi rantsuwa da rayuwar Annabi Muhammadu (ﷺ) cewa, suna cikin mayen sha'awa suna ɗimuwa da faganniya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana azabar da ta auka wa mutanen Annabi Luɗu da sassafe lokacin da rana take hudowa, sai wata tsawa mai tsanani mai girgiza ƙasa ta auka musu, Allah ya mayar da saman garin ya koma ƙasa, sannan ya bi su da ruwan duwatsu na wutar Jahannama.
Allah ya bayyana cewa, a game da wannan hallakarwar da ya yi wa mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lalle akwai ayoyi, watau abubuwan lura ga masu lura da hangen nesa da kyau, domin kufan gidajen waɗannan mutane yana nan a kan hanyar duk masu wucewa ta wannan gari. Lalle a cikin wannan abu da ya faru akwai ayoyi ga muminai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ƙaryata manzo ɗaya kamar ƙaryata dukkan manzanni ne.

2. Butulce wa ni'imomin Allah yana jawo fushinsa da uƙubarsa.

3. Dukiya da 'ya'ya da duk wani abu da mutum yake taƙama da shi na duniya ba za su amfane shi da komai ba yayin da azabar Allah ta zo masa.

Suratul Hijr (78-84)
وَإِن كَانَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأَيۡكَةِ لَظَٰلِمِينَ ٧٨ فَٱنتَقَمۡنَا مِنۡهُمۡ وَإِنَّهُمَا لَبِإِمَامٖ مُّبِينٖ ٧٩ وَلَقَدۡ كَذَّبَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡحِجۡرِ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٨٠ وَءَاتَيۡنَٰهُمۡ ءَايَٰتِنَا
فَكَانُواْ عَنۡهَا مُعۡرِضِينَ ٨١ وَكَانُواْ يَنۡحِتُونَ مِنَ ٱلۡجِبَالِ بُيُوتًا ءَامِنِينَ ٨٢ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلصَّيۡحَةُ مُصۡبِحِينَ ٨٣ فَمَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٨٤

78. Lalle kuma mutanen (alƙaryar) Mai duhuwa tabbas sun zamanto azzalumai.

79. Sai Muka azabtar da su, lalle kuma su biyun suna kan wani gwadabe ne fitacce.

80. Haƙiƙa kuma mutanen *Hijiru* (Samudawa) sun ƙaryata manzanni.

81. Muka kuma kawo musu ayoyinmu, sai suka zamanto masu bijirewa daga gare su.

82. Sun zamanto suna fafe duwatsu suna yin gidaje su zama cikin aminci.

83. Sai tsawa ta auka musu da asuba.

84. Sai abin da suka zamanto suna aikatawa bai amfane su ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi nuni zuwa ga ƙissar mutanen Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka zauna a wata alƙarya mai duhuwa. Sun zalunci kawunansu yayin da suka kafirce wa Allah suka kuma ƙaryata annabawa. Allah ya kama su da azaba mai tsanani ya hallaka su gaba ɗaya. Guraben gidajensu da na mutanen Annabi Luɗu suna nan a fili a kan hanyar matafiya.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da ƙissar Samudawa mutanen Annabi Salihu, watau mutanen Hijru, wani gari da ke tsakanin Hijaz da Sham. Sun ƙaryata duk manzanni, domin kuwa sun ƙaryata Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya bayyana cewa, ya nuna musu duk wata hujja da dalili da zai tabbatar musu da gaskiyar Annabi Salihu. Daga cikinsu har da taguwar da suka nema a fito masa da ita, amma sai suka bijire wa duk waɗannan hujjoji suka yi watsi da su. Hakanan ba su gode wa Allah a kan ni'imomin da ya yi musu ba, domin ya ba su ƙarfin jiki da lafiya har sun kasance suna fafe duwatsu suna yin gidaje da suke zaune a cikinsu amintattu babu abin da yake ba su tsoro.
Ya tabbata a wani hadisi, Annabi (ﷺ) ya wuce ta gidajen Samudawa a Hijru. An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kada ku shiga wurin waɗannan da aka saukar wa da azaba sai kuna kuka, idan ba za ku kasance masu kuka ba, to kada ku shiga wurarensu don kada abin da ya same su ku ma ya same ku." [Bukhari #433 da Muslim #2980].
Allah ya bayyana cewa, saboda wannan butulcin nasu ya hallaka su a lokacin da wata tsawa ta azaba ta afka musu da asuba ba zato ba tsammani. Abin da suka yi ta tarawa na dukiyoyi iri-iri da gidajensu na duwatsu da suka yi ta ginawa ba su kare su daga azabar Allah ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hikimar halittar sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu gaba ɗaya ita ce bautar Allah shi kaɗai ba tare da haɗa shi da abokin tarayya ba. Don haka Allah ya hallaka al'ummun da suka gabata saboda sun bijire wa wannan hikima ta Ubangiji.

2. Umarni da yin kyakkyawar afuwa wadda ba ta ƙunshe da cutarwa sai dai kyautatawa ga wanda ya munana.

3. Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama lokacin da za a yi wa kowa hukunci daidai da aikinsa ba za a zalunci kowa da komai ba.

4. Wajibi ne ga mai da'awa ya zamanto mai yawan haƙuri; kada mummunar mu'amalar waɗanda yake yi wa wa'azi gare shi ta tunzura shi ta sa ya fusata har ya munana musu mu'amala; ya yi haƙuri ya yafe

Suratul Hijr (85-86)

وَمَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّۗ وَإِنَّ ٱلسَّاعَةَ لَأٓتِيَةٞۖ فَٱصۡفَحِ ٱلصَّفۡحَ ٱلۡجَمِيلَ ٨٥ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ ٱلۡخَلَّٰقُ ٱلۡعَلِيمُ ٨٦

85. Ba Mu kuma halicci sammai da ƙasa ba sai da gaskiya. Kuma lalle alƙiyama tabbas mai zuwa ce, sai ka yi afuwa kyakkyawar afuwa.

86. Lalle Ubangijinka Shi ne Mai halitta, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna hikimar yin halitta gaba ɗaya da cewa, bai halicci sammai da ƙasa da abin da yake a tsakaninsu da abubuwan da suke cikinsu a banza ba; ya yi su ne don wata hikima mai girma, ya halicce su don gaskiya, watau don su nuna cikar ikon mahaliccinsu da yalwar rahamarsa da iliminsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da abokin tarayya ba. Sannan su tabbatar da cewa, alƙiyama gaskiya ce tana nan tafe. Ashe duk wanda ya iya halittar sammai da ƙasa da girmansu, ba zai gagare shi ya sake dawo da halittar mutum ba bayan mutuwa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi afuwa mai kyau, wadda babu cutarwa a cikinta; ya saka da kyakkyawa yayin da aka yi masa mummuna. Lalle Allah shi ne mahaliccin komai da kowa masanin duk wata halitta da ya yi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar *Suratul Fatiha* a cikin sauran surorin Alƙur'ani.

2. Kada mumini ya damu da kallon ƙyale-ƙyalen duniya da kafirai suke ciki, ya shagaltu da neman yardar mahaliccinsa da gina lahirarsa.

3. Har kullum mumini ya yi murna da 'yan'uwansa muminai da suke tare da shi, kada kuma bijirewar kafirai gare shi ta saka shi rayuwar damuwa da ƙunci.

4. Mumini ya kamata ya zamanto mai sauƙin kai da tawalu'u ga 'yan'uwansa muminai, mai nuna izzarsa da isarsa a gaban kafirai.

5. Yana da kyau mai kira zuwa ga Allah ya yi ta yi ba tare da yana waiwayen abin da maƙiya suke faɗa a kansa ba, domin shagalta da su zai hana shi gudanar da abin da ya kamata ya gudanar, zai ɓata masa lokacinsa.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin ɗaukar mummunan mataki a kan duk wani mai cin mutuncin Manzonsa (ﷺ) ko yi masa ɓatanci. Kuma a koyaushe Allah yana cika wa Manzonsa wannan alƙawari, domin babu lokacin da wani zai yi ɓatanci ga Manzon Allah (ﷺ) sai ya yi mummunan ƙarshe a rayuwarsa.

7. Babu abu mai magance wa mumini damuwarsa kamar ambaton Allah, watau zikiri da kuma salla. Shi ya sa ya tabbata a hadisi cewa, Annabi (ﷺ) idan wani abu ya dame shi sai ya yi salla. [Dubi, Abu Dawud #1321].

8. Babu wani lokaci da ibada gaba ɗayanta take sauka daga kan bawa matuƙar yana raye yana kuma cikin hankalinsa.

9. Salla ba ta sauka daga kan Musulmi matuƙar yana cikin hayyacinsa. Wajibi ne a kansa ya sallace ta gwargwadon ikonsa.

10. Tabbatar da ɓatan masu da'war cewa akwai wani mataki na walittaka da mutum zai kai ya daina bautar Allah gaba ɗaya. Wannan kafirci ne, domin annabawa da sahabbansu babu wanda ya kai su sanin Allah da

sanin haƙƙoƙinsa da yadda ake girmama shi, amma duk da haka sun fi kowa yawan bautar sa da aikata alheri har zuwa ranar mutuwarsu.

Suratul Hijr (87-99)

وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَٰكَ سَبۡعٗا مِّنَ ٱلۡمَثَانِي وَٱلۡقُرۡءَانَ ٱلۡعَظِيمَ ٨٧ لَا تَمُدَّنَّ عَيۡنَيۡكَ إِلَىٰ مَا مَتَّعۡنَا بِهِۦٓ أَزۡوَٰجٗا مِّنۡهُمۡ وَلَا تَحۡزَنۡ عَلَيۡهِمۡ وَٱخۡفِضۡ جَنَاحَكَ لِلۡمُؤۡمِنِينَ ٨٨ وَقُلۡ إِنِّيٓ أَنَا ٱلنَّذِيرُ ٱلۡمُبِينُ ٨٩ كَمَآ أَنزَلۡنَا عَلَى ٱلۡمُقۡتَسِمِينَ ٩٠ ٱلَّذِينَ جَعَلُواْ ٱلۡقُرۡءَانَ عِضِينَ ٩١ فَوَرَبِّكَ لَنَسۡـَٔلَنَّهُمۡ أَجۡمَعِينَ ٩٢ عَمَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩٣ فَٱصۡدَعۡ بِمَا تُؤۡمَرُ وَأَعۡرِضۡ عَنِ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ٩٤ إِنَّا كَفَيۡنَٰكَ ٱلۡمُسۡتَهۡزِءِينَ ٩٥ ٱلَّذِينَ يَجۡعَلُونَ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَۚ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ٩٦ وَلَقَدۡ نَعۡلَمُ أَنَّكَ يَضِيقُ صَدۡرُكَ بِمَا يَقُولُونَ ٩٧ فَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ وَكُن مِّنَ ٱلسَّٰجِدِينَ ٩٨ وَٱعۡبُدۡ رَبَّكَ حَتَّىٰ يَأۡتِيَكَ ٱلۡيَقِينُ ٩٩

87. Haƙiƙa kuma Mun ba ka (ayoyi) bakwai waɗanda ake ta nanatawa (wato *Suratul Fatiha*) da kuma Alƙur'ani mai girma.

88. Kada ka zura idanuwanka ga abubuwan jin daɗi da Muka ba wa wasu dangogi daga cikinsu, kada kuma ka yi baƙin ciki a kansu, kuma ka ƙasƙantar da kanka ga muminai.

89. Ka kuma ce: "Lalle ni, ni ne mai gargaɗi mabayyani".

90. Kamar yadda Muka saukar wa masu rarrabawa (wato ma'abota littafi).

91. (Su ne) waɗanda suka mai da Alƙur'ani kashi-kashi.

92. (Na rantse) da Ubangijinka tabbas za Mu tambaye su gaba ɗaya.

93. Game da abin da suka kasance suna aikatawa.

94. To ka tsage gaskiyar abin da aka umarce ka da shi, ka kuma kawar da kanka daga mushirikai.

95. Lalle Mu Mun isar maka (sharrin) masu izgili.

96. (Su ne) waɗanda suke sanya wani abin bauta tare da Allah. Ba ko da daɗewa ba za su sani.

97. Haƙiƙa kuma Muna sane da cewa ƙirjinka yana ƙunci game da abin da suke faɗa.

98. To sai ka yi tasbihi tare da godiyar Ubangijinka, ka kuma zamo cikin masu sujjada.

99. Ka kuma bauta wa Ubangijinka har yaƙini ya zo maka (wato mutuwa).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa, ya ba shi wasu ayoyi bakwai waɗanda a koyaushe ake maimaita karatunsu, su ne ayoyin *Suratul Fatiha* guda bakwai waɗanda kowane mai salla ta farilla ko nafila sai ya maimaita karatunsu a cikin raka'o'in sallarsa. Ya kuma ba shi Alƙur'ani mai girma wanda ya ƙunshi alherin duniya da na lahira, yake kuma bayyana wa ɗan'adam kyakkyawan tsari na rayuwa wanda yake cike da adalci da sanin yakamata.

An karɓo daga Abu Sa'id ɗan Al-Mu'alla (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya wuce ni ina salla, sai ya kirawo ni, amma ban amsa masa ba har sai da na gama salla sannan na je wurinsa, sai ya ce: "Me ya

hana ka zuwa gare ni?" Sai na ce: "Salla nake yi a lokacin." Sai ya ce: "Ashe ba Allah ya ce: 'Ya ku waɗanda suka yi imani, ku amsa kiran Allah, ku amsa wa Manzo idan ya kirawo ku' ba?" Annabi ya ci gaba da ce masa: "Shin ba na karantar da kai mafi girman sura ba a Alƙur'ani kafin in fita daga wannan masallacin?" Abu Sa'id ya ce: "Sai kuma ya kama hanya zai fita, sai na tuna masa, sai ya ce: "Ita ce (*Alhamdu lillahi Rabbil alamin*); su ne ayoyi bakwai waɗanda ake maimaita karatunsu da kuma Alƙur'ani mai girma da aka ba ni." [Bukhari #4474].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "*Ummul Ƙur'an* ita ce ayoyi bakwai da ake maimaita karatunsu da Alƙur'ani mai girma." [Bukhari #4704].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana Manzonsa ɗaga kai ya kalli ni'imomi na rayuwar duniya iri-iri da Allah ya ba wa kafirai suna fantamawa a cikinsu daidai da son ransu, suna kuma ƙaryata shi da butulce wa Allah. Duk wannan wani ƙyale-ƙyale ne na duniya mai gushewa, don haka kada ya damu da ƙaryata shi ko izgili da suke yi masa, ba wani alheri ko amfani tare da su. Ya mai da hankalinsa ga muminai da suke tare da shi sun ishe shi komai, ya kuma yi tawalu'u gare su.
Ya kuma umarce shi da ya dage a kan gargaɗin mutanensa daga azabar Allah, ya kuma bayyana musu cewa, shi mai bayyana gargaɗinsa ne a fili don kowa ya ji ya nutsu.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Misalina da misalin abin da Allah ya aiko ni da shi kamar misalin wani mutum ne da ya zo wa mutanensa ya ce musu: 'Ya ku mutanena, lalle ni na ga rundunar mahara da idona, kuma ni mai gargaɗi ne gare ku na musamman, don haka ku tsira da kanku, ku tsira da kanku.' Sai wasu daga cikin mutanensa suka ji maganarsa suka fita a farkon dare suka tafi a natse har suka tsira. Wasu kuma daga mutanensa suka ƙaryata shi, sai kuwa waɗannan mahara suka yi musu sammako suka hallaka su gaba ɗayansu. Wannan shi ne misalin wanda ya yi mini ɗa'a ya bi abin da na zo da shi, da kuma misalin wanda ya saɓa mini ya ƙaryata abin da na zo da shi na gaskiyar." [Bukhari #7283 da Muslim #2283].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da yi wa mushrikai kashedi da gargaɗi kan su guji abin da zai jawo musu azabarsa kamar yadda ya saukar da ita ga waɗanda suka rarraba littattafansu suka yi imani da wasu suka kafirce wa wasu, ko suka yi imani da wani ɓangare na littafi suka kafirce wa wani ɓangare. Su waɗannan mushrikai kuma siffanta Alƙur'ani suka yi da siffofi iri-iri; wani lokaci su ce tsafi ne, wani lokaci su ce bokanci ne, a wani lokaci kuma su kira shi waƙe. Allah ya yi wa Annabi rantsuwa da Zatinsa cewa, haƙiƙa sai ya yi wa waɗannan mutane gaba ɗayansu tambayoyi game da duk abin da suka aikata a nan duniya na saɓon Allah da kafirci.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tsaya ya tsage gaskiya, ya bayyana abin da aka umarce shi da shi na kira zuwa kaɗaita Allah da bauta da ƙaurace wa shirka, kuma kada ya damu da maganganun da mushirikai za su yi ta yi a kai. Kada kuma ya ji tsoron su, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne zai tsare shi daga makircin duk wani mai izgili daga cikin shugabannin kafirai na Ƙuraishawa. Allah ya bayyana su da cewa, sun yi nisa wajen rungumar gumaka suna bauta musu tare da Allah, ya kuma tabbatar musu da cewa, za su gane kurensu, don za su ga mummunan sakamakon ayyukansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabi cewa, ya san irin damuwar da yake ciki ta ƙaryata shi da kafirai suke yi, tare da yi masa izigili da cin zarafi iri-iri shi da sahabbansa. To sai ya sanar da shi abin da zai riƙa yi don cire wannan damuwar daga ransa, shi ne ya yi ta tsarkake Allah tare da yabon sa da gode masa, watau ya yawaita tasbihi da faɗar '*Alhamdu lillahi*', sannan ya shagalta da salloli na farilla da nafila.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Idan Annabi (ﷺ) yana cikin wata damuwa yakan ce:

" لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ الْعَظِيمُ الْحَلِيمُ۞ لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ رَبُّ الْعَرْشِ الْعَظِيمِ۞ لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ رَبُّ السَّمَاوَاتِ وَرَبُّ الْأَرْضِ وَرَبُّ الْعَرْشِ الْكَرِيمِ ".

Ma'ana: "Babu abin bautawa da gaskiya sai Allah mai girma mai haƙuri; babu abin bautawa da gaskiya sai Allah Ubangijin Al'arshi mai girma; babu abin bautawa da gaskiya sai Allah Ubangijin sammai kuma Ubangijin ƙasa kuma Ubangijin Al'arshi mai girma." [Muslim #7097].

Da waɗannan abubuwa ne zai magance duk wata damuwa da kafirai suka sa shi cikinta. Allah ya umarce shi da ya ci gaba da bautar sa babu ƙaƙƙautawa har ya cim ma dahir, watau mutuwa ta riske shi a kan haka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin faruwarsa nan gaba to kamar ma ya faru ne, domin Allah ya riga ya gama hukuncinsa lokaci kaɗai ake jira.

2. Kusantowar ranar alƙiyama, saboda bayyanar wasu daga cikin alamominta, kamar aiko da Annabi (ﷺ).

3. Wahayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa annabawansa shi ne ruhin da al'umma ba za ta rayu kyakkyawar rayuwa ba sai da shi.

4. Manzanci zaɓin Allah ne ga wanda ya ga dama cikin bayinsa.

5. Babban abin da dukan annabawa suka zo da shi shi ne tabbatar da Kaɗaitakar Allah wajen bauta da kuma nesanta haɗa shi da komai.

16-Suratun Nahl

Mabuɗin Surar:

1. Sunan Surar:
Ana kiran ta da suna "*Suratun Nahl*". *An-Nahlu* a harshen Larabci shi ne ƙudan zuma. An kira ta da wannan suna ne kuwa saboda a cikinta Allah ya yi maganar ƙudan zuma, a aya ta 68 zuwa ta 69. Sannan a cikin Alƙur'ani kakaf babu inda sunan ƙudan zuma ya zo sai a cikin wannan Surar.
Ana kuma kiran ta da sunan '*Suratun Ni'ami*', saboda a cikinta Allah ya ambaci ni'imomi da dama da ya yi wa ɗan'adam.
Amma dai abin da ke cikin Masahif, da littattafan Tafsiri da na Hadisai shi ne '*Suratun Nahl*'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya*, watau an saukar da ita kafin hijrar Annabi (ﷺ) zuwa Madina, a maganar yawancin malamai. Ibnu Abbas da As-Sha'abi sun togace ayoyinta uku na ƙarshe cewa su sun sauka ne a Madina, bayan an gama yaƙin Uhudu, an kashe Baffan Annabi (ﷺ) Hamza (Allah ya ƙara masa yarda) da wasu Musulmi, an kuma yi gunduwa-gunduwa da wani ɓangare na jikinsu. Wannan abu ya fusata Annabi (ﷺ) matuƙa, har ya ci alwashin cewa, duk lokacin da Allah Ya ba shi nasara a kan kafirai, to shi ma zai rama abin da aka yi musu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) Ya saukar da ayoyi ukun ƙarshe na wannan Sura. [Dubi, Tafsirin Ɗabari, Juzu'i na 14, shafi na 132, da Musnad Bazzar# 9530].
Wannan hadisi ne mai rauni. [Dubi, Ibn Kasir, Juzu'i na 4, shafi na 614].
Wasu kuma sun ce, daga aya ta 1 zuwa aya ta 40 *Makkiyya* ce. Daga aya ta 41 kuma har zuwa ƙarshen Surar *Madaniyya* ce.
Amma ra'ayin da ya fi shahara shi ne maganar cewa, *Makiyya* ce in ban da ayoyi uku na ƙarshe, su an saukar da su ne bayan hijra.

3. Jerin Saukarta:
Wannan Sura ta sauka bayan saukar da "*Suratul Anbiya'i*", gabanin saukar "*Suratus Sajda*". Ita ce Sura ta saba'in da biyu (72) a jerin saukar da surorin Alƙur'ani mai girma.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta ɗari ashirin da takwas ne (128).

5. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura ya haɗa da manya-manyan mas'aloli na imani da tabbatar da Ɗayantakar Allah wajen bauta da tabbatar da manzanci da kuma rayuwa bayan mutuwa.

6. Daga Cikin Abubuwa Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Batun Tauhidi da bayyana hujjoji a kan ɓacin hanyar shirka da Allah.
• Dalilai masu tabbatar da manzancin Annabi (ﷺ) da saukar masa da Alƙur'ani daga Allah.

• Tabbatar da cewa, shari’ar Musulunci ta kafu a kan ginshiƙai na addinin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
• Tabbatar da rayuwa bayan mutuwa da sakamakon ayyuka.
• Kafa hujjoji ta hanyar bayanin manya-manyan ni’imomi da Allah ya yi wa ɗan’adam a sama da ƙasa da ruwa da tudu.
• Gargaɗin kafirai game da azabar Allah wadda yake saukar da ita a kan waɗanda suka ƙaryata manzanninsa.
• Bayanin ni’imomin da ya tanadar wa muminai masu kiyaye dokokinsa waɗanda kuma suka yi haƙuri a kan cutarwar kafirai gare su, suka yi ƙaura daga garuruwansu don Allah.
• Umarni da riƙo da shikashikan shari’a, kamar adalci da kyautatawa da taimakon juna da cika alƙawari da guje wa munanan ayyuka da zalunci da warware alƙawari, da abin da Allah ya tanada na sakamako da alherin duniya da na lahira a kan haka.
• Kira zuwa ga tuba ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da bayanin hanyoyin da’awa zuwa ga Musulunci da lallashin Annabi (ﷺ) da ƙarfafa masa gwiwa shi da mabiyansa da cewa, Allah yana tare da su, zai taimaka musu, zai kuma ba su nasara.

Suratun Nahl (1-2)
أَتَىٰٓ أَمۡرُ ٱللَّهِ فَلَا تَسۡتَعۡجِلُوهُۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ١ يُنَزِّلُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ بِٱلرُّوحِ مِنۡ أَمۡرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦٓ أَنۡ أَنذِرُوٓاْ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱتَّقُونِ ٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Al’amarin Allah ya zo, don haka kada ku nemi gaggauto shi (watau ranar alƙiyama). Tsarki ya tabbata a gare Shi, Ya kuma ɗaukaka daga abin da suke tara (Shi da shi).

2. Yana saukar da mala’iku da wahayi na umarninsa ga waɗanda Ya ga dama daga bayinsa da cewa,: “Ku yi gargaɗi cewa,, lalle ba wani abin bauta sai Ni, to sai ku kiyaye dokokina.”

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da tabbatar wa kafirai cewa, ranar alƙiyama da suke yawan tambayar Manzon Allah (ﷺ) game da lokacin zuwanta, to lokacinta ya gabato kuma yana nan zai wakana babu makawa, don haka su daina neman a gaggauto da zuwansa.
Sai kuma ya bayyana musu cewa, ya tsarkaka daga duk wani abu da suke yin shirka da shi, watau jingina masa wasu abokan tarayya ko danganta shi ga ‘ya’ya ko mata da duk wani abu da ya saba da kamala.
Ya kuma bayyana cewa, shi ne yake saukar da mala’iku ɗauke da wahayi mai raya zukatan bayi, wanda yake ƙunshe da hukuncinsa ga wanda ya ga dama cikin bayinsa, su ne manzanninsa, ya kuma umarce su da su gargaɗi mutane game da aikata shirka, su nuna musu cewa, babu wani abin bauta da gaskiya sai Allah kaɗai, don haka su kiyaye dokokinsa, su aikata abin da ya wajabta musu su guji abin da ya hana su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk halittun Allah na sama da na ƙasa suna nuni ne ga Kaɗaitakar Allah.

2. Rahamar Allah ce ta sa ya hore mana dabbobi domin amfaninmu a rayuwarmu ta duniya.

3. Halaccin amfani da dabbobi don nuna ado da kwalliya. Don haka nishaɗantar da kai da abubuwan da Allah ya halatta amfani da su ba haramun ne ba.

4. Halaccin ɗora wa dabbobi kamar raƙuma da shanu da dawakai da alfadarai da jakuna kaya, amma bai halatta a ɗora wa dabba kayan da ya fi ƙarfinta ba.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi nuni zuwa ga abin da zai halitta bayan saukar Alƙur'ani na abubuwan hawa na ƙasa da ruwa da sama waɗanda sahabbai ba su san da su ba. Wannan ishara ta Ubangiji ta tabbata a yau bayan ɗan'adam ya ga wasu abubuwan hawa da ɗaukar kaya waɗanda a da bai san su ba, kamar mota da jirgin ƙasa da na sama da makamantansu. Wannan ɗaya ce daga mu'ujizojin Alƙur'ani.

6. Babu inda mutum zai sami bayanin hanyar gaskiya da ta ƙarya sai cikin abin da Allah ya saukar wa annabawansa na wahayi. Bin su shi ne shiriya, barin su shi ne taɓewa.

Suratun Nahl (3-9)

خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّۚ تَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ۝٣ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِن نُّطۡفَةٖ فَإِذَا هُوَ خَصِيمٞ مُّبِينٞ ۝٤ وَٱلۡأَنۡعَٰمَ خَلَقَهَاۖ لَكُمۡ فِيهَا دِفۡءٞ وَمَنَٰفِعُ وَمِنۡهَا تَأۡكُلُونَ ۝٥ وَلَكُمۡ فِيهَا جَمَالٌ حِينَ تُرِيحُونَ وَحِينَ تَسۡرَحُونَ ۝٦ وَتَحۡمِلُ أَثۡقَالَكُمۡ إِلَىٰ بَلَدٖ لَّمۡ تَكُونُواْ بَٰلِغِيهِ إِلَّا بِشِقِّ ٱلۡأَنفُسِۚ إِنَّ رَبَّكُمۡ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ ۝٧ وَٱلۡخَيۡلَ وَٱلۡبِغَالَ وَٱلۡحَمِيرَ لِتَرۡكَبُوهَا وَزِينَةٗۚ وَيَخۡلُقُ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ۝٨ وَعَلَى ٱللَّهِ قَصۡدُ ٱلسَّبِيلِ وَمِنۡهَا جَآئِرٞۚ وَلَوۡ شَآءَ لَهَدَىٰكُمۡ أَجۡمَعِينَ ۝٩

3. Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya. Ya ɗaukaka daga abin da suke tara (Shi da shi).

4. Ya halicci mutum daga maniyyi, sai ga shi mai jayayya a fili.

5. Ya kuma halicci dabbobin ni'ima. Kuna da (abin) ɗumama jiki tattare da su, da kuma sauran abubuwan amfani; daga gare su ne kuma kuke ci.

6. Kuma kuna da abubuwan ado a tattare da su, lokacin da kuke dawowa (daga kiwo) da kuma lokacin da kuke fita (da safe).

7. Suna kuma ɗaukar kayayyakinku masu nauyi zuwa garin da ba za ku iya isar sa ba sai da ƙyar. Lalle Ubangijinku tabbas Mai tausayi ne, Mai rahama.

8. Dawakai da kuma alfadarai da jakai (Ya halitta muku su) don ku hau su kuma su zama ado. Zai kuma hallici abin da ma ba ku sani ba.

9. Kuma bayanin hanya madaidaiciya haƙƙi ne a kan Allah, daga kuma (hanyar) akwai karkatacciya. Da kuma Ya ga dama lalle da Ya shirye ku gaba ɗaya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ɗimbin ni'imominsa ne da ya yi wa bayinsa a sama da ƙasa da tudu da ruwa. Waɗannan ni'imomi kuma dukkansu dalilai ne masu nuna Kaɗaitar Allah a Rububiyyarsa da Uluhiyyarsa. Don haka shi kaɗai ya cancanci bauta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara da bayanin halittar sammai da abin da yake cikinsu. Hakanan ya halicci ƙasa da abin da take ɗauke da shi, kuma ya yi halittarsu da gaskiya, watau domin su zamanto dalilai masu tabbatar da Kaɗaitakarsa da cancantar a bauta masa ba tare da haɗa komai da shi ba.
Sai kuma ya bayyana halittar ɗan'adam wanda shi ne mafi darajar halittunsa gaba ɗaya; ya halicce shi ne daga ɗigon maniyyi wulaƙantacce mai rauni, ya kuma tsara halittarsa mataki-mataki har ya cika daidaitaccen mutum, to amma bayan ya zo duniya sai ya kasance mai yawan jayayya a kan ƙarya don ya

kawar da gaskiya, kuma mai bayyana wannan hali a fili maimakon gode wa Allah a kan ni'imomin da ya yi masa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu ni'imomi da ya yi wa 'yan'adam bayan halittarsu a wannan duniya. Daga cikinsu akwai dabbobin ni'ima, watau raƙuma da shanu da tumakai da awakai; ya halicce su ne don amfanin 'yan'adam. Suna amfani da gashinsu wajen yin tufafin sawa don ɗumama jiki, da tatsar nononsu domin sha, da kuma cin namansu, har ma suna yin ado da su lokacin da dabbobin suke hutawa da yamma da lokacin da suke fita kiwo da safe.
Ya bayyana cewa, da waɗannan dabbobi mutane suke amfani wajen ɗaukar kaya masu nauyi a lokacin tafiye-tafiyensu zuwa wasu garuruwa masu nisan gaske waɗanda ba za su iya kaiwa gare su ba sai da ƙyar da gumin goshi. Don haka ya kamata su sani cewa, lalle Ubangijinsu mai tausayi ne mai jin ƙai; ya hore musu waɗannan dabbobi waɗanda suke da tsananin buƙatarsu a rayuwarsu.
Ya ci gaba da bayyana musu ni'imar wasu dabbobin da amfaninsu gare su, su ne dawakai da alfadarai da jakuna. Allah ya halitta musu su ne domin su hau, su ɗaukar musu kaya, kuma su yi ado da su. Baya ga waɗannan dabbobin hawan da ɗaukar kaya kuwa zai ma halicci wasu abubuwan da a wancan lokaci ba su san su ba.
Wannan ayar ba ta nuna haramcin cin naman doki ba, domin ta ambaci mafi yawancin amfanin da ake yi da waɗannan dabbobi ne. Sannan kuma an haɗa ambaton dawaki tare da alfadarai da kuma jakuna na gida da aka haramta cin namansu, domin larabawa ba su cika cin nama waɗannan dabbobi ba, domin ba su da yawa a yankinsu, kuma ga shi suna da buƙatar dawakai wajen yaƙe-yaƙensu. Don haka rashin ambaton cin namansu a nan ba ya nuna haramci ko kaɗan.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya hana cin naman jakunan gida, ya ba da izinin cin naman dawakai." [Bukhari #4219 da Muslim #1941].

An karɓo daga Asma'u 'yar Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ta ce: "Mun yanka doki mun ci a zamanin Manzon Allah (ﷺ) a Madina." [Muslim #1942].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi ne ya ɗora wa kansa nauyin bayanin hanya madaidaiciya da za ta kai bayinsa zuwa ga samun yardarsa da kyakkyawan sakamakonsu, watau bayanin addinin Musulunci gare su. Amma akwai wasu karkatattun hanyoyi na Shaiɗan, waɗanda duk wanda ya bi su, to za su raba shi da gaskiya, kamar hanyoyin Yahudu da Nasara da maguzawa da mushirikai.
Sannan ya bayyana cewa, duk waɗannan suna wakana ne da ikonsa da ganin damarsa. Da a ce ya ga dama da ya shiryar da mutane gaba ɗaya zuwa ga addinin Musulunci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mumini yakan ga darussa da izina cikin duk wata ni'ima da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi.

2. Waɗanda ba sa hango girman Kudurar Allah da Ɗayantakarsa daga halittun da ya yi a sama da ƙasa, mutane ne marasa kan gado da tunani.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ni'imta mu da hore mana ruwan kogi domin mu ci naman kifayen da ke cikinsa, mu fito da duwatsun cikinsa masu daraja kamar lu'u-lu'u da murjani sannan mu hau jiragen ruwa su yi yawo da mu a kansa domin tafiya fatauci da yaƙin kare kai daga maƙiya da 'yan ta'adda.

4. Halaccin cin naman dabbobin ruwa kamar kifi da makamancinsa.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci taurari a sama don yi mata ado da amfani da su ga matafiya da masu lissafin watanni da shekara.

Suratun Nahl (10-16)

هُوَ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً لَّكُم مِّنْهُ شَرَابٌ وَمِنْهُ شَجَرٌ فِيهِ تُسِيمُونَ ۝١٠ يُنۢبِتُ لَكُم بِهِ ٱلزَّرْعَ وَٱلزَّيْتُونَ وَٱلنَّخِيلَ وَٱلْأَعْنَـٰبَ وَمِن
كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ ۗ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَةً لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ۝١١ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ ۖ وَٱلنُّجُومُ مُسَخَّرَٰتٌۢ بِأَمْرِهِۦٓ ۗ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَـٰتٍ
لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ۝١٢ وَمَا ذَرَأَ لَكُمْ فِى ٱلْأَرْضِ مُخْتَلِفًا أَلْوَٰنُهُۥٓ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَةً لِّقَوْمٍ يَذَّكَّرُونَ ۝١٣ وَهُوَ ٱلَّذِى سَخَّرَ ٱلْبَحْرَ لِتَأْكُلُوا۟ مِنْهُ لَحْمًا
طَرِيًّا وَتَسْتَخْرِجُوا۟ مِنْهُ حِلْيَةً تَلْبَسُونَهَا ۖ وَتَرَى ٱلْفُلْكَ مَوَاخِرَ فِيهِ وَلِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ۝١٤ وَأَلْقَىٰ فِى ٱلْأَرْضِ رَوَٰسِىَ أَن
تَمِيدَ بِكُمْ وَأَنْهَـٰرًا وَسُبُلًا لَّعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ۝١٥ وَعَلَـٰمَـٰتٍ ۚ وَبِٱلنَّجْمِ هُمْ يَهْتَدُونَ ۝١٦

10. Shi ne wanda Ya saukar da ruwa daga sama; daga gare shi ne kuke sha, daga gare shi ne kuma bishiyoyi suke (sha) wanda da su ne kuke kiwon (dabbobinku).

11. Da shi (ruwan) Yake tsiro muku da shuke-shuke da zaitun da dabinai da inabai da kuma kowanne irin ‘ya’yan itace. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga mutanen da suke tunani.

12. Ya kuma hore muku dare da rana da kuma wata; taurari ma ababen horewa ne da umarninsa. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu hankali.

13. Da kuma abubuwan da Ya halitta muku a ƙasa masu launi iri daban-daban. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga mutanen da suke wa'azantuwa.

14. Shi ne kuma wanda Ya hore muku kogi don ku ci daddaɗan nama mai taushi daga gare shi, ku kuma riƙa fito da kayan ado daga cikinsa waɗanda kuke ɗaurawa, kuma ka ga jiragen ruwa suna keta shi don kuma ku nema daga falalarsa (Ubangiji) don kuma ku riƙa godiya.

15. Ya kuma sanya wa ƙasa turaku don kada ta riƙa tangal-tangal da ku da kuma ƙoramu da hanyoyi don ku riƙa gane (inda kuka dosa).

16. Da kuma alamomin (hanya). Da kuma taurari ne suke gane (inda suka dosa).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana ɗimbin ni’imomin da ya yi wa ‘yan’adam. Ya saukar musu da ruwan sama wanda suke sha suke shayar da dabbobinsu. Da shi ne kuma bishiyoyi suke tsirowa waɗanda dabbobinsu suke ci suna kiwo. Da wannan ruwan sama ne, har ila yau, Allah yake fitar musu da shuke-shukensu na abincinsu da zaitun da inabai da dabinai da kowane irin ‘ya’yan itatuwa. Lalle a cikin halittar waɗannan abubuwa akwai ayoyi masu nuna ikon Allah ga mutanen da suke tunani cikin halittarsa domin kafa dalili da ita a kan cikar Kudurarsa da girmansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ni’imarsa ta hore wa ‘yan’adam dare wanda suke hutawa a cikinsa su yi barci, ya kuma hore musu rana domin su fita neman abinci a cikinta. Don haka ya tabbatar musu da cewa, duk kuma manya-manyan halittunsa na sama, kamar rana da wata da taurari, ya hore musu su da umarninsu, su ba su haske su yi amfani da su wajen gane lissafi da kuma tafiyar dare da sauransu. Lalle cikin wannan aiki na Ubangiji akwai ayoyi bayyanannu ga mutane masu hankaltar abubuwa yadda suke.
Sannan kuma ya ambaci cewa, daga cikin ni’imominsa na bayan ƙasa akwai abubuwan ban mamaki da ya halitta masu launi iri-iri, kamar dabbobi da ma’adanai da tsirrai da duwatsu masu kamanni daban-daban

da amfani iri-iri. Lalle cikin wannan aiki na Allah akwai bayyanannun ayoyi ga mutanen da suke wa'azantuwa da gaskiyar da ake faɗa musu, su gode wa Allah ni'imomin nan da ya yi musu.
Sai kuma har wa yau, ya ambaci wasu ni'imomin na halitta da ya yi a ruwa. Wato ya hore wa 'yan'adam ruwan kogi domin samun amfani iri-iri daga cikinsa. Sukan kamo kifi su ci daddaɗan namansa mai taushi, kuma su riƙa fito da kayan ado daga cikinsa waɗanda suke sawa su da matansu, kamar lu'u-lu'u da murjani. Sannan kuma ga jiragen ruwa manya da ƙanana suna keta ruwa ɗauke da mutane kuma maƙare da kaya, amma ba tare da sun nutse ba. To su sani cewa, Allah ya hore musu waɗannan jirage ne domin su yi amfani da su wajen fita neman arziƙi da kasuwanci kuma domin su gode masa bisa ga waɗannan ni'imomin da ya ba su su kuma kaɗaita shi da bauta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sake ambaton wasu ni'imomin nasa ga 'yan'adam waɗanda ko su kaɗai ma sun isa su tabbatar musu da cikar Kudurarsa da cancantar a kaɗaita shi da bauta. Shi ne wanda ya kafa manya-manyan duwatsu a cikin ƙasa domin su hana ta tangal-tangal da su, ya kuma gudanar da ƙoramu a kanta domin su sami ruwan sha da na shayar da dabbobinsu da shuke-shukensu. Ya kuma fitar musu da hanyoyin tafiye-tafiyensu bai rufe su da duwatsu da ƙoramu ko itatuwa ba. Ya yi musu haka ne domin su sami isa duk inda suke son zuwa. Ya kuma ƙara musu da sanya wasu alamomi bayyanannu a kan ƙasa waɗanda za su taimaka musu wajen gane hanya, kamar duwatsu da tuddai da kwari don su taimaka wa matafiyi wajen tantance inda ya dosa. Da daddare kuwa sai ya sanya musu taurari su ne alamomin da za su yi amfani da su wajen gane hanyoyi don kada su ɓace.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yin halitta dalili ne da yake nuna cancantar bauta, don haka bai kamata a bauta wa wani wanda bai halicci komai ba; Allah kaɗai za a bauta wa domin shi ne mahaliccin komai.

2. Duk wata halitta kewaye take ta ko'ina da ni'imomin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka babu wanda zai iya ƙididdige ni'imomin Allah gare shi ballantana ya iya bayar da haƙƙin godiya a kansu gaba ɗaya. Saboda haka ko'ina bawa ya kai wajen bauta wa Allah to ba zai iya biyan bashin godiya da yake kansa ba, sai dai falalar Allah ta sa ya yi masa afuwa.

3. Wajibi ne a kan bawa ya kyautata niyyarsa da ayyukansa a koyaushe, ya zamanto mai tsoron Allah a sarari da ɓoye domin shi ne masanin sarari da ɓoye.

4. Duk masu ƙaryatawa da ranar lahira ba suna ƙaryatawa ne ba saboda rashin gamsassun dalilai a kan hakan; suna yin haka ne saboda gurɓacewar zukatansu da lalacewar ɗabi'unsu da kuma tsabar girman kai da rashin miƙa wuya.

5. Girman zunubin mai girman kai da mummunan sakamakonsa a lahira wanda shi ne wutar Jahannama.

6. Kamar yadda Allah yake son wasu daga cikin bayinsa saboda nagartarsu, to hakanan yake ƙin wasu daga cikinsu saboda munanan halayensu, kamar girman kai. Don haka nuna soyayya da ƙiyayya siffa ce daga cikin siffofin Allah maɗaukaki.

Suratun Nahl (17-23)
أَفَمَن يَخۡلُقُ كَمَن لَّا يَخۡلُقُۚ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ١٧ وَإِن تَعُدُّواْ نِعۡمَةَ ٱللَّهِ لَا تُحۡصُوهَآۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَغَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٨ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا تُسِرُّونَ وَمَا تُعۡلِنُونَ ١٩
وَٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَا يَخۡلُقُونَ شَيۡـٔٗا وَهُمۡ يُخۡلَقُونَ ٢٠ أَمۡوَٰتٌ غَيۡرُ أَحۡيَآءٖۖ وَمَا يَشۡعُرُونَ أَيَّانَ يُبۡعَثُونَ ٢١ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۚ فَٱلَّذِينَ
لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ قُلُوبُهُم مُّنكِرَةٞ وَهُم مُّسۡتَكۡبِرُونَ ٢٢ لَا جَرَمَ أَنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعۡلِنُونَۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُسۡتَكۡبِرِينَ ٢٣

17. Yanzu wanda Yake halitta (zai yi) daidai da wanda ba ya halitta? Yanzo ba kwa wazantu ba?

18. Idan kuma da za ku ƙirga ni'imar Allah to ba za ku iya ƙididdige ta ba. Lalle Allah tabbas Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

19. Allah kuma Ya san abin da kuke ɓoyewa da abin da kuke bayyanawa.

20. Waɗannan kuma suke bauta wa ba Allah ba, ba sa iya halittar komai, su ne ma ake halittar su.

21. Matattu ne su ba rayayyu ba; ba sa kuma sanin sanda za a tashe su.

22. Abin bautarku Abin bauta ne Ɗaya, sai dai waɗanda ba sa yin imani da ranar lahira zukatansu masu musun hakan ne, kuma su masu girman kai ne.

23. Ba shakka, lalle Allah Yana sane da abin da suke ɓoyewa da abin da suke bayyanawa. Lalle Shi ba Ya son masu girman kai.

A waɗannan ayoyi, bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilai masu nuna samuwarsa da cikar ikonsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai saboda ɗimbin ni'imomin da ya saukar wa bayinsa daga sama da waɗanda ya fitar musu daga ƙasa, ayyukan da babu wani daga cikin allolinsu da zai iya yin ɗaya daga cikinsu, sai kuma ya nuna wa mushirikai ɓacin hanyar da suke kai ta bautar wanin Allah wanda ba ya iya halittar komai suna daidaita shi da Allah mahaliccin komai da kowa. Me ya sanya ba su tuna girman Allah su kaɗaita shi da bauta, kada su yarda su haɗa bautarsa da wani wanda ba zai iya halittar komai ba?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa mutane cewa, ni'imominsa da ya yi musu masu yawa ne ainun, ko sun yi ƙoƙarin lissafa su to ba za su iya ƙididdige su ba saboda matuƙar yawansu da rabe-rabensu. To amma duk da haka yana gafarta wa wanda ya yi sakaci wajen godiyar ni'imar da ya yi masa, yana tausaya masa, ya ci gaba da kwararo masa ni'imominsa duk kuwa da rashin cancantarsa ga hakan.
Sannan Allah ya bayyana wasu daga cikin siffofinsa maɗaukaka waɗanda in ba shi ba babu wani abin bauta da ya siffanta da su. Ya tabbatar wa bayinsa cewa, ya san abin da suke ɓoyewa na ayyukansu ya kuma san waɗanda suke bayyanawa, zai kuma yi musu sakayya a kansu gaba ɗaya. To amma waɗanda mushirikai suke bauta wa babu abin da suka iya halitta komai ƙanƙantarsa. Hasali ma dai su masu bauta musu ɗin ne suka ƙera su da hannayensu, don haka wane irin rashin hankali ne ya sa suke bauta wa gumakan da su ne suka sassaƙa ko suka gina su da hannayensu? Sannan kuma wani abin lura har ila yau shi ne, waɗannan gumakan wasu daskararrun abubuwa ne marasa rai balle ilimin sanin wani abu na rayuwa; ba su san lokacin da za a tashe su tare da masu bautar su ba, domin a jefa su cikin wutar Jahannama gaba ɗaya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, daga duk bayanan da suka gabata ya tabbata cewa, abin bautarsu guda ɗaya ne ba shi da abokin tarayya, shi ne Allah. To amma waɗanda ba su yi imani akwai lahira ba zukatansu na cike da musunta Kaɗaitakar Allah saboda rashin tsoron Allah da ya cika su, don haka ba su yi imani da akwai wani hisabi ko uƙuba ba, ga su kuma da ɗan karen girman kai wanda ya hana su karɓar gaskiya, ya hana su miƙa wuya.
Sai ya ƙara tabbatar musu da cewa, tabbas yana sane da duk ayyukansu da suke ɓoyewa da waɗanda suke bayyanawa, babu abin da bai sani ba, zai kuma yi musu sakayya a kai, sannan su sani cewa, tabbas shi Allah ba ya son duk wani mai girman kai mai ƙin bautarsa ko miƙa wuya ga umarninsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Duk wani mai girman kai kwatankwacin ƙwayar zarra a zuciyarsa ba zai shiga Aljanna ba." Wani mutum ya ce: "Ya Manzon Allah, tabbas mutum yana son tufarsa ta zamanto mai kyau, takalminsa mai kyau." Sai Annabi (ﷺ) ya ce:

“Lalle Allah mai kyau ne yana son kyakkyawa. Girman kai shi ne ƙin gaskiya da wulaƙanta mutane.” [Muslim #91 da Tirmizi #1999].

An karƀo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Za a tashi masu girman kai a tattaro su ranar alƙiyama suna kamar tururuwa a kamannin mutane, saboda ƙankantarsu komai ya kere su, a haka za su shiga wani kurkuku a Jahannama mai suna Bulasu, wuta mai tsananin ƙuna za ta baibaye su, za a kuma shayar da su ruwan mugunyar ‘yan wuta.” [Ahmad #6677 da Tirmizi #2492].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya butulce wa mafi girman ni’ima da Allah ya yi masa, watau ni’imar shiriya da karantarwa ta Alƙur’ani, to wannan ba zai taƀa gode wa wata ni’ima ta Allah ba.

2. Girman laifin wanda ya ƙirƙiri wata ƀarna wasu kuma suka bi shi a kanta.

3. Yana daga cikin wasa da hankali da Shaiɗan yake yi wa wasu, su riƙa ɗaukar bin hukuncin abin da Allah ya saukar a littafinsa wani ci-baya ne da rashin wayewa.

4. Ɓatattu suna ƀatar da wanda ya jahilci cewa su ƀatattu ne. Makircinsu yana yin tasiri ne kawai a kan marasa hankali kuma wawayen jahilai. Wannan kuwa babban abin zargi ne gare su, domin maimakon su shiryar da jahilai sai suka daɗa dulmiyar da su.

5. Duk mai gina ramin mugunta ƙarshe shi ne zai faɗa cikinsa, sannan a lahira ya gamu da azabar Allah wadda ba iyaka.

6. Falalar masu ilimi, masu faɗar gaskiya masu shiryarwa, kuma Allah zai karƀi shaidarsu da sauran mutane.

7. Ladabin mala’iku ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Dubi yadda suka mayar da sani ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ba su ce: “Mu ma mun san abin da kuke aikatawa ba”, domin su nuna cewa, duk wani abu da suka sani Allah ne ya sanar da su.

8. Kowaɗanne masu ayyukan laifi suna da ƙofarsu ta musamman da za su shiga wutar Jahannama daga gare ta.

Suratun Nahl (24-29)

وَإِذَا قِيلَ لَهُم مَّاذَآ أَنزَلَ رَبُّكُمْ قَالُوٓاْ أَسَٰطِيرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٢٤﴾ لِيَحْمِلُوٓاْ أَوْزَارَهُمْ كَامِلَةً يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ وَمِنْ أَوْزَارِ ٱلَّذِينَ يُضِلُّونَهُم بِغَيْرِ عِلْمٍ ۗ أَلَا سَآءَ مَا يَزِرُونَ ﴿٢٥﴾ قَدْ مَكَرَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ فَأَتَى ٱللَّهُ بُنْيَٰنَهُم مِّنَ ٱلْقَوَاعِدِ فَخَرَّ عَلَيْهِمُ ٱلسَّقْفُ مِن فَوْقِهِمْ وَأَتَىٰهُمُ ٱلْعَذَابُ مِنْ حَيْثُ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٢٦﴾ ثُمَّ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يُخْزِيهِمْ وَيَقُولُ أَيْنَ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ كُنتُمْ تُشَٰٓقُّونَ فِيهِمْ ۚ قَالَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلْعِلْمَ إِنَّ ٱلْخِزْىَ ٱلْيَوْمَ وَٱلسُّوٓءَ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٧﴾ ٱلَّذِينَ تَتَوَفَّىٰهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ ظَالِمِىٓ أَنفُسِهِمْ ۖ فَأَلْقَوُاْ ٱلسَّلَمَ مَا كُنَّا نَعْمَلُ مِن سُوٓءٍ ۚ بَلَىٰٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٢٨﴾ فَٱدْخُلُوٓاْ أَبْوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۖ فَلَبِئْسَ مَثْوَى ٱلْمُتَكَبِّرِينَ ﴿٢٩﴾

24. Idan kuma aka ce da su: “Me Ubangijinku Ya saukar?” (Sai) su ce: “Tatsuniyoyin mutanen farko.”

25. (Wannan kuwa) don su ɗauki laifukansu cikakku ranar alƙiyama, da kuma laifukan waɗanda suke ƀatarwa ba da ilimi ba. Ku saurara, abin da suke ɗauka ya munana!

26. Haƙiƙa waɗanda suka gabace su sun shirya makirci, sai Allah Ya tumɓuke gininsu daga harsashi, sai rufin ya rifto a kansu daga samansu, azaba kuma ta zo musu ta inda ba sa tsammani.

27. Sannan kuma ranar alƙiyama (Allah) zai kunyata su kuma zai ce: “Ina abokan tarayyar nawa da kuka zamanto kuna jayayya a game da su?” (Sai) waɗanda aka bai wa ilimi su ce: “Lalle a yau wulaƙanci da mummunar azaba sun tabbata a kan kafirai.”

28. Waɗanda mala’iku suke karɓar ransu suna masu zaluntar kawunansu; sai suka ba da kai (suna cewa,): “Ba mu kasance muna yin wani mummunan aiki ba.” A’a, ba haka ba ne, lalle Allah Masanin abin da kuka zamanto kuna aikatawa ne.

29. “Sai ku shiga ƙofofin Jahannama kuna masu dawwama a cikinta; lalle makomar masu girman kai ta munana.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda mushirikai masu musunta Kaɗaitakar Allah da ƙaryata ranar lahira suke kuma ƙaryata Annabi (ﷺ) tare da kafirce wa Alƙur’ani, suke mayar da martani duk sanda za a tambaye su mene ne Allah ya saukar wa Muhammadu (ﷺ)? Sai su amsa da cewa, babu abin da Allah ya saukar masa; duk abin da yake karanta musu ƙarairayinsa ne da tatsuniyoyin mutanen da. Don haka suka kafirce masa suka kuma ja mabiyansu zuwa ga kafirci da ƙaryata Annabi (ﷺ). Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon wannan mummunan aiki nasu ranar alƙiyama, da cewa za su zo suna ɗauke da laifuffukansu cikakku a wannan ranar da kuma laifuffukan mutanen da suka ɓatar suka hana su karɓar Musulunci saboda jahilci da makauniyar biyayyar da suka yi musu. Allah kuma ya yi tir da wannan mummunan laifi da suke dakonsa har lahira.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wanda ya yi kira zuwa ga shiriya, to yana da lada kamar na waɗanda suka bi shi, hakan kuma ba zai rage komai daga nasu ladan ba. Wanda kuma ya yi kira zuwa ga ɓata, to yana da zunubi kamar na waɗanda suka bi shi, hakan kuma ba zai rage komai daga nasu zunubban ba.” [Muslim #2674].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wani makirci da kafirai suke ƙulla wa Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa da addininsa a kansu zai ƙare, domin kafirai a gabaninsu sun yi wa manzanni irin waɗannan ƙulle-ƙullen makirci, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tumɓuke ginin makircinsu daga harsashinsa sai rufinsa ya rufta a kansu, sai kuma ga wata azaba Allah ya aiko musu da ita ta inda ba sa tsammani, domin a zatonsu gine-ginensu za su kare su daga azaba, sai ga shi Allah ya hallakar da su gaba ɗaya da waɗannan gine-gine nasu.
Wannan azabar duniya ce, amma a lahira kuwa to Allah zai wulaƙanta su ya ƙasƙantar da su, zai tambaye su ina waɗanda suke bauta wa tare da shi waɗanda a dalilin ƙaunarsu ya sa suke gaba da annabawan Allah da muminai: Me ya hana su kawo musu ɗauki su cece su daga azabar Allah? To amma babu wata amsa da za su iya bayarwa a lokacin, sai malamai masana Allah su amsa da cewa,: Lalle kunyata da wulaƙanci da mummunar azaba a ranar nan sun tabbata a kan kafirai.
Sai ya bayyana cewa, waɗanda suka cancanci waccan azaba su ne kafirai waɗanda suka kafe a kan kafirci har zuwa lokacin da mala’ikan mutuwa da mala’iku masu dafa masa suka zo karɓar rayukansu suna cikin kafirci dumu-dumu. To a nan ne za su miƙa wuya suna nuna biyayya, su kuma fito fili su ƙaryata kafircin da suka kasance a kai, su nuna su fa ba su taba yin wani mummunan aiki ba; suna zaton wannan gardamar za ta yi musu amfani. To a nan ne za a ƙaryata su a tunatar da su cewa, a rayuwarsu ta duniya su masu munanan ayyuka ne, kuma sun manta Allah masanin duk abin da suka riƙa aikatawa ne na kafirci da saɓon Allah, kuma sai ya yi musu sakayya a kansu ɗaya bayan ɗaya. Domin gaɓoɓinsu ne za su bayar da shaida a

kan kafircinsu sai kawai a umarce su da shiga wutar Jahannama ta ƙofar da aka tanada domin masu laifi irin nasu, su yi ta zama a cikinta dindindin babu ranar fitowa. Allah kuma ya yi tir da wannan mummunar makomar ta masu girman kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muminai su ne a koyaushe suke ganin cewa, abin da addininsu ya kawo musu shi ne alheri da albarka da ci gaba a rayuwarsu, ba sa fifita wani abu a kansa. Saɓanin maƙiya Allah waɗanda suke ɗaukar koyarwar Alƙur'ani da sunnar Annabi (ﷺ) a matsayin ci baya da rashin wayewa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa muminai alƙawarin kyautata rayuwarsu ta duniya kafin ta lahira, matuƙar sun kyautata imaninsu da ayyukansu, sannan a lahira ma zai yi musu mafi kyawun sakamako.

3. Muminai suna samun albishir da Aljanna tun lokacin mutuwarsu daga bakin mala'iku masu ɗaukan rayukansu.

4. Yana daga cikin karamcin Allah da yawan kyautarsa yakan ba wa 'yan Aljanna duk abin da suka nema, har ma ya tunatar da su wasu ni'imominsa waɗanda ba su yi tunaninsu ba.

5. Muminai za su shiga Aljanna ne saboda ayyukansu na ƙwarai, wannan kuwa zai faru ne gare su da rahama ta Allah da falalarsa, ba don ƙarfinsu ko dabararsu ba.

Suratun Nahl (30-32)

*وَقِيلَ لِلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ مَاذَآ أَنزَلَ رَبُّكُمۡۚ قَالُواْ خَيۡرٗاۗ لِّلَّذِينَ أَحۡسَنُواْ فِي هَٰذِهِ ٱلدُّنۡيَا حَسَنَةٞۚ وَلَدَارُ ٱلۡأٓخِرَةِ خَيۡرٞۚ وَلَنِعۡمَ دَارُ ٱلۡمُتَّقِينَ ٣٠ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ يَدۡخُلُونَهَا تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ لَهُمۡ فِيهَا مَا يَشَآءُونَۚ كَذَٰلِكَ يَجۡزِي ٱللَّهُ ٱلۡمُتَّقِينَ ٣١ ٱلَّذِينَ تَتَوَفَّىٰهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ طَيِّبِينَ يَقُولُونَ سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمُ ٱدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٣٢

30. Aka kuma ce da waɗanda suka kiyaye dokokin (Allah): "Me Ubangijinku Ya saukar?" Suka ce: "Alheri." Waɗanda suka kyautata a wannan duniya suna da kyakkyawar (rayuwa). Lalle kuma gidan lahira shi ya fi alheri. Madalla da gidan masu taƙawa.

31. Aljannatai ne na jin daɗi za su shige su, ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu; suna da duk abin da suka ga dama cikinsu. Kamar haka Allah Yake saka wa masu taƙawa.

32. Waɗanda mala'iku suke ɗaukar ransu suna tsarkaka, suna cewa: "Aminci ya tabbata a gare ku, ku shiga Aljanna saboda abin da kuka zamanto kuna aikatawa (a duniya).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffar muminai masu tsoron Allah da kiyaye dokokinsa ta hanyar aiki da umarninsa da barin haninsa. Su kam, duk lokacin da aka tambaye su, mene ne Ubangijinsu ya saukar wa Annabinsu, sai su amsa da cewa,: Ya saukar masa da alheri mai girma. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk waɗanda suka kyautata ibadarsu kuma suka kyautata mu'amalarsu da mutane a wannan rayuwar ta duniya, to suna da kyakkyawan sakamako da zai tanadar musu. Zai ba su yalwar arzuki a nan duniya da nasara a kan abokan gabarsu. Sannan abin da ya tanadar musu na kyakkyawan sakamakon lahira ya fi wannan na duniya, domin sakamakonsu a can gidan Aljanna ne wanda ni'imominsa ba sa yankewa. Tabbas wannan gida madalla da shi. Domin Aljanna ce ta zama har abada, za su shige ta, ƙoramu na gudana ta ƙarƙashin manyan gine-ginenta da bishiyoyinta, za su sami duk

wani abin da rayukansu suke sha’awa na abinci da abin sha da tufafi da sauran buƙatunsu, an yi musu tanadinsu. Sai ya bayyana cewa, da irin wannan gwaggwaɓan sakamakon ne zai saka wa masu kiyaye dokokinsa, suna aikata abin da ya umarce su suna kuma barin abin da ya hana su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin waɗannan bayi nasa muminai lokacin da mala’ikun mutuwa za su zo karɓar rayukansu suna tsarkaka babu wata shirka a tare da su; zukatansu sun tsarkaka da sanin Allah da ambatonsa; mala’ikun suna yi musu sallama tare da cewa, a yau ba za su haɗu da wata tawaya ba, suna umartarsu da shiga gidan Aljanna saboda ayyukansu a duniya na riƙo da kyakkyawar aƙida da aiki na ƙwarai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mai hankali shi ne wanda yake wa’azantuwa daga abin da ya sami wani mai mummunan aiki irinsa da ya gabace shi.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba azzalumin kowa ba ne. Duk wanda bai ga da kyau ba to shi ne ya ja wa kansa, domin Allah cikakken mai adalci ne ba zai taɓa cutar da marar laifi ba.

3. Yin izgili ga masu kira zuwa ga Allah da faɗar gaskiya abu ne mai matuƙar haɗari ga mai yinsa.

Suratun Nahl (33-34)
هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّآ أَن تَأۡتِيَهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَوۡ يَأۡتِيَ أَمۡرُ رَبِّكَۚ كَذَٰلِكَ فَعَلَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ وَمَا ظَلَمَهُمُ ٱللَّهُ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٣٣
فَأَصَابَهُمۡ سَيِّـَٔاتُ مَا عَمِلُواْ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٣٤

33. Shin akwai abin da (mushrikai) suke sauraro in ban da mala’iku su zo musu, ko kuma umarnin Ubangijinka ya zo? Kamar haka waɗanda ke gabaninsu suka aikata. Allah bai zalunce su ba, sai dai kuma kawunansu suka kasance suna zalunta.

34. Sai (sakamakon) mummunan abin da suka aikata ya same su, kuma abin da suke yi wa izgili ya rutsa da su.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa, shin mushirikai ba za su ji gargaɗin da ake yi musu ba, su bar miyagun ayyukansu da maganganunsu, har sai lokacin da za su ga mala’ikun mutuwa sun zo karɓar rayukansu, su riƙa dukan fuskokinsu da bayansu. Ko kuma lokacin da Allah zai ba da umarnin a hallaka su tun a nan duniya ba tare da wani daga cikinsu ya kai labari ba?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, miyagun ayyukan da mushirikai suke yi ba su ne farau ba; akwai waɗanda suka gabace su sun yi irin waɗannan miyagun ayyuka Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su, kuma idan ya yi musu hakan ba zaluntar su ya yi ba, su ne dai suka zalunci kawunansu da aikata kafirci wanda ya kai su ga halaka. Sai mummunar uƙubar miyagun ayyukansu ta auka musu, kuma azabar da suke yi wa izgili a duk lokacin da aka tsoratar da su da ita sai ga shi ta kewaye su ta ko’ina ba mafita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafa hujja da ƙaddara a kan saɓon Allah tafarki ne na mushirikan farko.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko da manzanninsa don yanke wa ɗan’adam hanzari.

3. Babban aikin manzanni shi ne isar da saƙon Allah. Don haka sun cika aikinsu yadda ya kamata ba su ɓoye komai ba na saƙon da aka umarce su da su bayyana.

4. Haramtawa da halattawa haƙƙin Allah ne shi kaɗai.

5. Allah ya aika wa kowace al'umma da ya halitta manzanni. Kuma dukkan manzannin Allah sun haɗu a kan kira zuwa ga Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta da barin bautar wasu ba Allah ba.

6. Shiriya tana hannun Allah, yana shiryar da duk wanda ya zaɓi shiriya daga cikin bayinsa, wanda kuma ya yi wa kansa mummunan zaɓi, to babu mai iya shiryar da shi.

7. Kimsa imani a zuciya ba aikin wani annabi ba ne; aikinsa kawai shi ne isar da saƙo.

8. Allah ya yi umarni da yin tafiye-tafiye domin ganin garuruwan kafiran farko da ya hallaka domin ɗaukar darasi da izina ba domin buɗe ido da shaƙatawa ba.

Suratun Nahl (35-37)

وَقَالَ ٱلَّذِينَ أَشۡرَكُواْ لَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَا عَبَدۡنَا مِن دُونِهِۦ مِن شَيۡءٖ نَّحۡنُ وَلَآ ءَابَآؤُنَا وَلَا حَرَّمۡنَا مِن دُونِهِۦ مِن شَيۡءٖۚ كَذَٰلِكَ فَعَلَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ فَهَلۡ عَلَى ٱلرُّسُلِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٣٥ وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ فَمِنۡهُم مَّنۡ هَدَى ٱللَّهُ وَمِنۡهُم مَّنۡ حَقَّتۡ عَلَيۡهِ ٱلضَّلَٰلَةُۚ فَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ٣٦ إِن تَحۡرِصۡ عَلَىٰ هُدَىٰهُمۡ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَن يُضِلُّ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٣٧

35. Waɗanda kuma suka yi shirka suka ce: "Da Allah Ya ga dama da ba mu bauta wa komai ba sai Shi, daga mu har iyayenmu, da kuma ba mu haramta komai ba wanda bai haramta ba." Kamar haka waɗanda suka gabace su suka aikata. Shin akwai abin da yake a kan manzanni in ban da isar da aike a fili?

36. Haƙiƙa kuma Mun aiko manzo a kowacce al'umma cewa,: "Ku bauta wa Allah, kuma ku nisanci Ɗagutu." To akwai daga cikinsu waɗanda Allah Ya shiryar, akwai kuma daga cikinsu wanda ɓata ya tabbata a kansa. To ku yi tafiya a bayan ƙasa ku ga yadda ƙarshen masu ƙaryatawa ya kasance.

37. Idan ma kana kwaɗayin shiriyarsu ne, to lalle Allah fa ba Ya shiryar da wanda Ya ɓatar; ba su da kuma wasu mataimaka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana faɗa mana yadda mushirikai suka riƙa yaudarar kawunansu suna kafa wa Allah hujja da ƙaddara a kan shirkar da suke yi, suna nuna cewa, Allah ne ya ga dama su bauta wa wasu gumaka tare da shi, wai domin da bai ga dama ba da ba su yi haka ba, kuma da sun bauta masa shi kaɗai; ba ma su kaɗai ba har ma iyayensu da ba su yi shirka ba, kuma da ba su haramta wa kansu wani abu wanda Allah bai haramta musu ba. To kuwa tun da har sun aikata waɗannan abubuwa, kuma babu wata azaba da Allah ya yi musu, to wannan a ganinsu yana nuna yardarsa da duka abubuwan da suka yi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, wannan hujjar tasu ta banza ce, domin kafiran da suka gabace su ma sun faɗi irin wannan magana, to amma daga ƙarshe Allah ya hallakar da su da azabarsa. Da a ce hujjarsu gaskiya ce to da Allah bai hallaka kafiran farko ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, nauyin da kawai yake kan manzanni shi ne su isar da saƙon da ya aiko su da shi. Idan sun yi haka to babu wata sauran hujja ga wanda saƙonsu ya je masa, sannan manzanni babu ruwansu da wanda zai kafa hujja da ƙaddara a kan wani mummunan aikinsa.
Sai kuma ya bayyana cewa, babu wata al'umma a bayan ƙasa sai da ya aika mata da manzo wanda ya umarci al'ummarsa su bauta wa Allah shi kaɗai, su bar bautar gumaka da shaiɗanu, sai ya zamanto a cikin al'ummarsa akwai wanda Allah ya datar da shi ya yi imani da wannan manzon ya bi shi sau-da-ƙafa. A cikinsu kuma akwai wanda ya kafirce ya bijire wa wannan manzo bai samu gam da katar ba, don haka ɓata ya tabbata a kansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da tafiya a bayan ƙasa, domin kowa ya gane wa idanunsa makomar masu ƙaryata manzannin Allah, ya ga yadda Allah ya saukar musu da azabarsa ta hallaka su baki ɗaya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Annabi (ﷺ) a kan yadda yake ta ƙoƙari yana kuma damuwa matuƙa wajen ya ga mutanensa duk sun shiriya sun karɓi gaskiya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa, duk irin ƙoƙarin da zai yi na ya ga sun shiriya, da duk irin hanyoyin da zai bi don ya fahimtar da su gaskiya, to ya sani cewa, wanda Allah bai so shi da shiriya ba ba zai taɓa shiriya ba, saboda ya riga ya yi wa kansa mummunan zaɓi. Sannan kuma ya bayyana masa cewa, waɗannan mutanen masu ƙaryata shi ba su da mai taimaka musu ya kare su daga azabar Allah sa'adda ta zo musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafiran Kuraishawa sun yarda da samuwar Allah amma ba su yarda zai iya sake raya matattu bayan sun ratattake sun zama ƙasusuwa ba.

2. Bayanin hikimar tashin alƙiyama, watau domin Allah ya bayyana gaskiya da ƙarya da duk wani abu da mutane suke jayayya a kansa a nan duniya.

3. Bayanin sauƙin aikata komai a wajen Allah, babu abin da yake gagarar sa.

Suratun Nahl (38-40)
وَأَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ لَا يَبۡعَثُ ٱللَّهُ مَن يَمُوتُۚ بَلَىٰ وَعۡدًا عَلَيۡهِ حَقّٗا وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٣٨ لِيُبَيِّنَ لَهُمُ ٱلَّذِي يَخۡتَلِفُونَ فِيهِ وَلِيَعۡلَمَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَنَّهُمۡ كَانُواْ كَٰذِبِينَ ٣٩ إِنَّمَا قَوۡلُنَا لِشَيۡءٍ إِذَآ أَرَدۡنَٰهُ أَن نَّقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٤٠

38. Suka kuma rantse da Allah iya rantsuwarsu, (cewa) Allah ba zai tashi wanda ya mutu ba. A'a, ba haka ba ne, alƙawari ne a kansa na gaskiya, sai dai yawancin mutane ba sa sanin (haka).

39. (Zai tashe su) don Ya bayyana musu abin da suke saɓani game da shi, don kuma kafirai su san cewa, su sun tabbata maƙaryata.

40. Abin da kawai Muke cewa da abu idan Mun nufe shi, sai Mu ce da shi: "Kasance", sai kawai ya kasance.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ruɗani da mushirikai suka riƙa yaɗawa don nuna cewa, ba sa buƙatar aiko musu wani manzo, domin har rantsuwa suke yi iyakar rantsuwarsu cewa, Allah ba zai tashi wani matacce ba, don haka babu batun wani hisabin ayyukansu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa, tabbas Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tashe su, domin wannan alƙawari ne na gaskiya da ya ɗaukar wa kansa, shi kuwa ba ya saɓa alƙawari, sai dai yawancin mutane ba su san haka ba, shi ya sa suke ƙaryatawa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, sai ya tashe su gaba ɗayansu domin ya bayyana musu gaskiyar abin da suke saɓawa a kansa, watau sha'anin Tauhidi da Alƙur'ani da annabta, kuma kafirai su tabbatar da cewa, su maƙaryata ne game da sanya wa Allah kishiyoyi da suka yi da ƙaryata batun tashin matattu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cikakken ikonsa a kan aikata duk abin da ya ga dama, babu wani abu da zai gagare shi a sama ko a ƙasa. Idan ya yi nufin raya matattu da tashinsu, to babu abin da zai hana shi aiwatar da haka, domin abin da kawai zai ce da wannan abu shi ne 'samu' sai nan take wannan abu ya samu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin yin ƙaura daga garin kafirci zuwa garin Musulunci yayin da aka hana Musulmi bautar Allah a wannan garin.

2. Girman ladan waɗanda suka yi hijira don Allah.

3. Falalar sahabban Annabi (ﷺ) waɗanda suka yi hijira daga Makka zuwa Habasha sannan zuwa Madina suka bar iyalansu da gidajensu da dukiyoyinsu domin neman yardar Allah da taimaka wa Annabi (ﷺ) wajen yaɗa addinin Musulunci.

4. Duk wanda ya kyautata aikinsa a nan duniya to Allah zai jiyar da shi daɗi na duniya, sannan ya yi masa babban sakamako a lahira na gidan Aljanna.

5. Girman ladan haƙuri a kan bin Allah da barin saɓa masa, da haƙuri a kan ƙaddara marar daɗi.

6. Falalar dogaro ga Allah cikin dukkan al'amuran bawa.

7. Zaɓaɓɓu a wajen Allah su ne idan wani abu ya dame su sai su yi haƙuri, idan ya fi ƙarfinsu sai su dogara ga Allah.

Suratun Nahl (41-42)
وَٱلَّذِينَ هَاجَرُواْ فِي ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا ظُلِمُواْ لَنُبَوِّئَنَّهُمۡ فِي ٱلدُّنۡيَا حَسَنَةٗۖ وَلَأَجۡرُ ٱلۡأٓخِرَةِ أَكۡبَرُۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٤١ ٱلَّذِينَ صَبَرُواْ وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ يَتَوَكَّلُونَ ٤٢

41. Waɗanda kuma suka yi hijira saboda Allah bayan an zalunce su lalle za Mu shirya musu kyakkyawar (rayuwa) a duniya; ladan lahira kuma ya fi girma da a ce sun kasance suna sane da (haka).

42. Waɗanda suka yi haƙuri kuma ga Ubangijinsu kawai suke dogaro.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka yi imani da shi da duka abin da ya aiko Annabinsa da shi, suka kuma yi hijira daga garuruwansu suka bar dukiyoyinsu da iyalansu don Allah, bayan kafirai sun addabe su da zalunci sun hana su bautar Allah; Allah kuma ya yi musu alƙawarin ba su kyakkyawan masauki a nan duniya da za su rayu a cikin izza da ɗaukaka, sannan ya yi musu tanadin wani sakamako na lahira wanda ya fi na nan duniya, watau gidan Aljanna. Sai kuma ya bayyana girman wannan ladan da cewa, da a ce kowa ya san yadda wannan lada yake to da babu wanda zai zauna bai yi hijira ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana siffofin waɗannan masu hijira da cewa, su ne waɗanda suka yi haƙuri a kan cutarwar da mutanensu suka yi musu; suka haƙura suka bar iyalansu da gidajensu da dukiyoyinsu, suka jure wajen bin Allah da Manzonsa, tare da dogara da Allah shi kaɗai cikin dukkan al'amuransu. To wannan ne ya sa Allah ya ba su wannan gwaggwaɓan ladan mai yawa.

An karɓo daga Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) , ya kasance idan ya ba wa wani muhajiri haƙƙinsa na dukiyar Baitil Mali sai yakan ce: "Karɓi wannan, Allah ya yi maka albarka, shi ne abin da Allah ya yi maka alƙawarinsa a nan duniya, amma abin da ya ajiye maka a lahira ya fi wannan, da a ce sun sani." [Ibn Jarir, *Tafsir*, Juzu'i na 17 shafi na 206].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah yana aiko da manzanni maza ne ba mata ba, ba kuma mala'iku ba.

2. Bayanin falalar masu ilimi, kuma ilimin da ya fi kowanne shi ne ilimin sanin Littafin Allah.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci duk wanda bai sani ba ya tambayi malamai a kan duk wani abu da ya taso na addini da rayuwa.

4. Bayanin zamantowar malamai adalai a wurin Allah don haka ne ma ya yi umarni a tambaye su, kuma da tambayarsu ne wanda bai sani ba zai sauke nauyi da zargi daga kansa, wannan yana nuna Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aminta da su.

5. Mafifita a cikin malamai su ne waɗanda suke san Alƙur'ani da abin da ya ƙunsa na hukunce-hukuncen shari'a da rayuwa, don haka su ne suka fi cancantar a kira su malamai.

6. Wajibi ne a kan duk wanda zai yi tambaya ya nemi wanda yake kyautata zaton yana cikin masana Alƙur'ani. Bai halatta gare shi ya riƙa tambayar wasu ba don kawai yana sa ran zai samu amsar da ta dace da son ransa daga gare su.

7. Alƙur'ani shi ne mafificin zikiri, don haka karanta shi ya fi kowane zikiri falala.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Annabi (ﷺ) Alƙur'ani sannan ya ɗora masa nauyin bayanin abin da ya zo cikinsa a dunƙule wanda yake buƙatar ƙarin bayani. Don haka babu mai fahimtar Alƙur'ani fahimta ta gaskiya sai ya haɗa da sunnar Annabi (ﷺ); idan bai yi haka ba to ya saki Alƙur'ani gaba ɗaya ya kuma ɓace hanya.

9. Ya kamata ga duk mai saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kasance a koyaushe mai tsoron azabar Allah ta sauko masa ba tare da ya ankara ba.

10. Dukkan halittu na sama da ƙasa suna sujjada ga Allah, sujjada ta haƙiƙa, kowace halitta gwargwadon yadda sujjadarta take.

11. Sujjadar halittu iri biyu ce:

Ta farko, sujjada ta tilas wadda take nuna cikar ikon Allah ga bayinsa. Wannan ta haɗa duk wani mahaluƙi mumini da kafiri, mai biyayya da marar biyayya, mutum da dabba.
Ta biyu, sujjada ta zaɓi, ita ce sujjadar waliyyan Allah da sauran bayin Allah muminai.

Suratun Nahl (43-50)

وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ إِلَّا رِجَالٗا نُّوحِيٓ إِلَيۡهِمۡۖ فَسۡـَٔلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلذِّكۡرِ إِن كُنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ ٤٣ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَٱلزُّبُرِۗ وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلذِّكۡرَ لِتُبَيِّنَ لِلنَّاسِ مَا نُزِّلَ إِلَيۡهِمۡ وَلَعَلَّهُمۡ يَتَفَكَّرُونَ ٤٤ أَفَأَمِنَ ٱلَّذِينَ مَكَرُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن يَخۡسِفَ ٱللَّهُ بِهِمُ ٱلۡأَرۡضَ أَوۡ يَأۡتِيَهُمُ ٱلۡعَذَابُ مِنۡ حَيۡثُ لَا يَشۡعُرُونَ ٤٥ أَوۡ يَأۡخُذَهُمۡ فِي تَقَلُّبِهِمۡ فَمَا هُم بِمُعۡجِزِينَ ٤٦ أَوۡ يَأۡخُذَهُمۡ عَلَىٰ تَخَوُّفٖ فَإِنَّ رَبَّكُمۡ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٌ ٤٧ أَوَ لَمۡ يَرَوۡاْ إِلَىٰ مَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ يَتَفَيَّؤُاْ ظِلَٰلُهُۥ عَنِ ٱلۡيَمِينِ وَٱلشَّمَآئِلِ سُجَّدٗا لِّلَّهِ وَهُمۡ دَٰخِرُونَ ٤٨ وَلِلَّهِ يَسۡجُدُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ مِن دَآبَّةٖ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَهُمۡ لَا يَسۡتَكۡبِرُونَ ٤٩ يَخَافُونَ رَبَّهُم مِّن فَوۡقِهِمۡ وَيَفۡعَلُونَ مَا يُؤۡمَرُونَ ٥٠

43. Ba Mu taɓa aiko (wasu manzanni) ba a gabaninka sai mazaje waɗanda Muke yi wa wahayi. Don haka ku tambayi ma’abota ilimi idan kun kasance ba ku sani ba.

44. (Mun aiko su) da hujjoji bayyanannu da littattafai. Mun kuma saukar maka da Alƙur’ani don ka yi wa mutane bayanin abin da aka saukar musu ko sa yi tunani.

45. Yanzu waɗanda suka shirya mummunan makirci ba sa gudun Allah Ya kife ƙasa da su, ko kuma azaba ta zo musu ta inda ba sa zato?

46. Ko kuwa Ya kama su a cikin kai-kawonsu, ba kuwa za su gagara ba?

47. Ko kuma Ya kama su a lokacin da suke cike da tsoron (Sa)? To lalle Ubangijinka Mai tausayi ne, Mai jin ƙai.

48. Shin yanzu ba sa ganin abubuwan da Allah Ya halitta kowane iri ne, inuwowinsa suna bazuwa dama da hagu, suna masu sujjada ga Allah suna kuma masu ƙaskantar da kai?

49. Abin da yake cikin sammai da abin da yake bayan ƙasa na kowace dabba da mala’iku suna yin sujjada ne ga Allah, su kuma ba sa girman kai.

50. Suna tsoron Ubangijnsu daga samansu kuma suna aikata abin da ake umartar su da shi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata babbar hujja da mushirikai suka riƙe suke ganin babu kamarta don ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da ƙin yarda da abin da ya zo musu da shi na shiriya. Watau a ganinsu babu yadda za a yi Allah ya aiko musu da mutum irinsu a matsayin manzo. Da a ce da gaske ne Allah zai aiko wani manzo to da sai ya aiko mala’ika ba mutum ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani a kan haka, ya tabbatar wa da Annabi (ﷺ) cewa, bai taɓa aiko da wasu manzanni a gabaninsa ba sai mazaje daga cikin mutane irinsu waɗanda ya riƙa aika musu da wahayi. Don haka bai taɓa aiko da wani mala’ika a matsayin manzo zuwa ga mutane ba. Wannan shi ne aikin Allah a koyaushe. Idan har suna tantama a kan hakan to su tambayi masana abin da littattafan farko suka ƙunsa na ilimi domin su tabbatar musu da gaskiyar wannan batu, idan har su ba su sani ba.

Sannan Allah ya bayyana abin da ya aiko waɗannan manzanni da shi, watau ya aiko su da hujjoji bayyanannu da littattafan da ya saukar musu. Kuma ya tabbatar a cikin dukkan waɗannan littattafai ba a taɓa aiko wa mutane wani manzo mala’ika ba.

Sai kuma ya tabbatar da cewa, shi ne ya saukar da Alƙur’ani ga Manzon Allah (ﷺ) domin ya zamanto wa’azi da tunatarwa ga mutane, kuma ya ɗora wa Annabi (ﷺ) nauyin yi musu bayani filla-filla na abubuwan da ya ƙunsa masu buƙatar ƙarin bayani, don mutane su yi tunani su fahimci abin da ya zo da shi su wa’azantu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da waɗannan kafirai masu ƙaryata Annabinsa (ﷺ) da nau'o'in azaba iri-iri da za su iya auka musu idan ba su tuba sun daina kafirci ba, sun kuma daina shirya mummunan makirci don su hana bin hanyar Allah. Ya yi musu kashedi da cewa, yanzu ba sa gudun ya kife ƙasa da su irin yadda ya yi wa Karuna a zamanin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ko ya aiko musu da wata azaba ta inda ba sa zato ba sa tsammani, kuma ya sauko musu da ita a lokacin tafiye-tafiyensu na neman abin duniya ba kuma za su gagare shi ba ko su kuɓuce masa. Ko kuma ya kama su da azaba a lokacin da suke cike da tsoron kamunsa? To Allah mai iya azabtar da su ne a kowane hali suke ciki idan ya ga dama. Sai dai ya ƙyale su bai yi musu hakan ba, saboda shi mai tausayi ne mai rahama, yakan jinkirta wa azzalumi amma duk sa'adda ya damƙe shi to ba zai iya kuɓucewa ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman lamarinsa da cikar ikonsa da yadda komai ya rusuna masa ya miƙa wuya gare shi; duk halittu gaba ɗaya na sama da ƙasa da mala'iku da mutum da aljan duk suna ƙarƙashin gudanarwarsa sai yadda ya yi da su; duk wani abu mai inuwa da inuwarsa take bazuwa dama da hauni, watau safe da yamma to inuwar wannan abin ma tana sujjada ne ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Malamai sun ce: Idan rana ta gushe daga tsakiyar sama to komai yana faɗuwa ya yi sujjada ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), suna masu ƙaskantar da kai gare shi. Haka kuma duk abin da yake cikin sammai da duk wani abu mai tafiya a bayan ƙasa mutum ne ko dabba, da dukkan mala'iku suna yi wa Allah sujjada shi kaɗai, ba sa girman kai wajen bautarsa, tare da wannan bautar tasu kuma, suna jin tsoron Ubangijinsu wanda yake sama da su da Zatinsa da ikonsa, suna kuma aikata abin da duk aka umarce su da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da Kaɗaitakar Allah wajen bauta.
2. Wanda ya cancanta a bauta masa a yi masa biyayya ta ƙarshe shi ne wanda ya halicci sama da ƙasa da abin da yake cikinsu, shi ne Allah Ɗaya.

3. Duk wata ni'ima da bawa zai samu a rayuwarsa, to daga Allah ne, shi ne mai bayar da ni'ima na haƙiƙa.

4. Ɗan'adam ba shi da mafaka don yaye masa wata cuta ko damuwa sai wajen Allah, yana ta kururuwar roƙon sa domin ya san shi kaɗai ne mai ikon kawar masa da damuwarsa.

5. Wanda shi ne ya kaɗaita wajen ba wa mutane abin da suke buƙata da yaye musu damuwarsu shi ne wanda ya cancanta su bauta masa shi kaɗai. To amma yawancin mutane suna butulce wa wannan ni'imar ta Allah, suna zaluntar kawunansu, idan sun shiga tsanani su roƙi Allah shi kaɗai, amma idan sun samu sauƙi suna cikin walwala sai su riƙa haɗa shi da wasu wajen bauta.

Suratun Nahl (51-55)
*وَقَالَ ٱللَّهُ لَا تَتَّخِذُوٓاْ إِلَٰهَيۡنِ ٱثۡنَيۡنِۖ إِنَّمَا هُوَ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ فَإِيَّيَ فَٱرۡهَبُونِ ٥١ وَلَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَلَهُ ٱلدِّينُ وَاصِبًاۚ أَفَغَيۡرَ ٱللَّهِ
تَتَّقُونَ ٥٢ وَمَا بِكُم مِّن نِّعۡمَةٖ فَمِنَ ٱللَّهِۖ ثُمَّ إِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فَإِلَيۡهِ تَجۡـَٔرُونَ ٥٣ ثُمَّ إِذَا كَشَفَ ٱلضُّرَّ عَنكُمۡ إِذَا فَرِيقٞ مِّنكُم بِرَبِّهِمۡ
يُشۡرِكُونَ ٥٤ لِيَكۡفُرُواْ بِمَآ ءَاتَيۡنَٰهُمۡۚ فَتَمَتَّعُواْ فَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ٥٥

51. Allah kuma Ya ce: "Kada ku riƙi abubuwan bauta guda biyu. Abin bauta Ɗaya Yake Tilo; to sai ku ji tsoro na Ni kaɗai."

52. Kuma abin da ke sammai da ƙasa nasa ne, kuma gare Shi ake biyayya tutur. Shin yanzu wanin Allah ne kuke yi wa taƙawa?

53. Kuma duk abin da kuke da shi na ni’ima to daga Allah ne; sannan kuma idan cuta ta same ku to wurinsa kuke kai kuka.

54. Sannan kuma lokacin da Ya yaye muku cutar sai a samu wata ƙungiya daga cikinku suna yin shirka da Ubangijinsu.

55. Don su butulce wa abin da Muka ba su. To ku ɗan ji daɗi a (duniya), sai dai ba da daɗewa ba za ku sani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da gargaɗin masu haɗa shi da wasu abubuwa wajen bauta, ya yi kira ga ɗaukacin bayinsa da kada su riƙi abubuwan bauta guda biyu, watau kamar majusawa masu cewa wai akwai allan alheri shi ne haske, akwai kuma na sharri shi ne duhu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, shi kaɗai ne abin bauta na gaskiya babu wani na biyunsa, don haka su tsorace shi shi kaɗai kada su ji tsoron waninsa kamar yadda suke jin tsoronsa.
Ya kuma bayyana musu cewa, duk abin da yake cikin sammai da wanda yake ƙasa shi ne mahaliccinsa mamallakinsa mai gudanar da lamuransa shi kaɗai ba tare da wani yana taya shi ba. Don haka su gane cewa, shi kaɗai ake yi wa tabbatacciyar biyayya da tsantsanta bauta da ƙasƙantar da kai gare shi a koyaushe. To yanzu bayan duk sun san waɗannan abubuwa, ta yaya za su ci gaba da tsoron wanin Allah har su riƙa bautarsa ba Allah ba? Suna jin tsoron kada ya raba su da wata ni’ima da suke ciki ne? Sai ya tabbatar musu cewa, duk wata ni’ima da mutane suke ciki ta addini ko ta rayuwa, to daga Allah take shi kaɗai babu mai tarayya da shi a kanta. Sannan idan wata cuta ta same su ta rashin lafiya ko talauci duka gare shi kaɗai suke komawa su yi ta roƙon sa domin ya yaye musu, don sun san babu mai yaye wata cuta sai shi. Don haka wanda shi kaɗai ne mai ba su alheri kuma ya yaye musu sharri ashe ba shi kaɗai ya wajaba su bauta wa ba wani ba?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana butulcin kafirai da cewa, idan ya amsa musu addu’o’insu ya yaye musu damuwarsu, to a maimakon su gode masa sai wasu daga cikinsu su koma su ci gaba da shirka, suna bautar waninsa tare da shi. To yanzu wannan wane irin butulci ne?! Don haka Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da su da cewa, su je su ci gaba da more jin daɗin duniya sai dai ba da daɗewa ba za su sani, lokacin da azabar Allah za ta zo musu a lahira ko ma tun a nan duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mummunan butulci ne bawa ya yi amfani da ni’imar da Allah ya yi masa wajen saɓa masa.

2. Duk mai ƙagar ƙarya yana jingina wa Allah da sunan addini ko waninsa, to ya riƙa tuna cewa, lalle akwai ranar da Allah zai yi masa tambaya a kan wannan ƙaryar kuma ba shi da mafita, babu kuma mai kare shi daga azabar Allah.

3. Faɗawa cikin baƙin ciki don an haifa wa mutum ‘ya mace ɗabi’a ce ta kafirai, wajibi ne mumini ya guje ta. Malam Katada yana cewa,: “Wannan aikin mushirikan Larabawa ne, Allah ya labarta mana mummunan aikinsu ne. Amma abin da ya dace da mumini shi ne ya yarda da rabon da Allah ya ba shi, abin da Allah ya hukunta wa bawa ya fi abin da bawa ya hukunta wa kansa, domin tabbas bai san cewa, wannan alheri ne gare shi ba. Sau da yawa ‘ya mace takan fi ɗa namiji zama alheri ga ‘yan’uwanta. Allah ya labarta muku halinsu ne domin ku nisance shi, domin ɗayansu yakan ciyar da karensa amma ya binne ‘yarsa da rai.” [Ibn Jarir, *Tafsir*, Juzu’i na 17, shafi na 228].

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffantu da siffofin kamala, babu tawaya ko kaɗan a cikin siffofinsa. Don haka duk wata kamala to Allah ne ya fi cancantarta; duk kuma wata nakasa da aibi Allah ne ya fi cancanta a kore masa shi.

Suratun Nahl (56-60)

وَيَجۡعَلُونَ لِمَا لَا يَعۡلَمُونَ نَصِيبٗا مِّمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡۗ تَٱللَّهِ لَتُسۡـَٔلُنَّ عَمَّا كُنتُمۡ تَفۡتَرُونَ ٥٦ وَيَجۡعَلُونَ لِلَّهِ ٱلۡبَنَٰتِ سُبۡحَٰنَهُۥ وَلَهُم مَّا يَشۡتَهُونَ ٥٧
وَإِذَا بُشِّرَ أَحَدُهُم بِٱلۡأُنثَىٰ ظَلَّ وَجۡهُهُۥ مُسۡوَدّٗا وَهُوَ كَظِيمٞ ٥٨ يَتَوَٰرَىٰ مِنَ ٱلۡقَوۡمِ مِن سُوٓءِ مَا بُشِّرَ بِهِۦٓۚ أَيُمۡسِكُهُۥ عَلَىٰ هُونٍ أَمۡ يَدُسُّهُۥ فِي ٱلتُّرَابِۗ أَلَا سَآءَ مَا يَحۡكُمُونَ ٥٩ لِلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ مَثَلُ ٱلسَّوۡءِۖ وَلِلَّهِ ٱلۡمَثَلُ ٱلۡأَعۡلَىٰۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٦٠

56. Suna kuma sanya wani kaso daga abin da Muka arzuta su da shi ga abubuwan da ba su san komai ba. Wallahi tabbas za a tambaye ku game da abin da kuka kasance kuna ƙirƙira.

57. Suna kuma jingina wa Allah ‘ya’ya mata, tsarki ya tabbata a gare Shi, su kuma suna da abin da suke sha'awa (na ‘ya’ya maza).

58. Kuma idan aka yi wa ɗayansu albishir da (‘ya) mace sai fuskarsa ta yi baƙi ƙirin yana cike da tsananin baƙin ciki.

59. Yana ɓuya daga (idon) mutane saboda munin abin da aka yi masa albishir da shi. Shin zai riƙe shi ne a wulaƙance ko kuwa zai binne shi ne a cikin ƙasa? Ku saurara, abin da suke hukuntawa kam ya munana.

60. Waɗanda ba sa imani da ranar lahira suna da mummunar siffa. Allah kuwa Yana da maɗaukakiyar siffa. Kuma Shi ne Mabuwayi Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana jahilcin mushirikai da ƙaryar da suke yi wa Allah, suna zaɓar wasu daga cikin dabbobinsu su ce na gumakansu ne tare da sun san cewa, Allah ne ya halicci waɗannan dabbobi ba gumakansu ba, shi ne ya arzuta su da su, amma maimakon su gode masa sai suke amfani da su wajen yi masa shirka, kamar yadda ya bayyana a *Suratul An’am*, aya ta 136. Allah ya yi rantsuwa da Zatinsa mai tsarki cewa, lalle sai ya tambaye su game da wannan ƙarya da suke ƙagawa, kuma zai yi musu mummunar uƙuba a kai.
Sannan kuma Allah ya ci gaba da bayanin wata kwamacala ta mushirikai da baƙin jahilcin rashin sanin girman Allah, shi ne yadda suka riƙa jingina wa Allah ‘ya’ya mata, suna cewa, mala’iku mata ne kuma ‘ya’yan Allah ne. Suna zaɓa wa Allah abin da su ba sa so wa kawunansu, domin suna ƙyamar haihuwar ‘ya mace. Tsarki ya tabbata ga Allah game da abin da suke jingina masa na ‘ya’ya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana irin mummunan halin da ɗayansu yake samun kansa a ciki duk lokacin da aka yi masa albishir da haihuwar ‘ya mace, yakan zauna cikin matsananciyar damuwa, fuskarsa ta yi murtuk yana cike da jin haushin abin da aka haifa masa. Don jin halin taskun da ya shiga har yakan ɓuyar wa ‘yan’uwansa don kada su gan shi su yi masa dariya na rashin samun ɗa namiji; daga nan ya shiga halin tararrabi yana tunanin yadda zai ɓullo wa lamarinsa, ko dai ya bar wannan jaririya da rai, idan kuwa ya yi haka zai ci gaba da rayuwa cikin wulaƙanci da ƙasƙanci a tsakanin mutanensa, ko kuma ita ta rayu cikin ƙasƙanci da wulaƙanci saboda ita ‘ya mace ce babu mai ƙaunarta balle ya darajta ta. Ko kuma ya binne ta da rai domin ya kuɓutar da kansa daga wulaƙanci da baƙin ciki, ita ma ta kuɓuta daga wulaƙanci da baƙin ciki. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir da irin wannan ɗanyen hukunci da suke yi na rashin imani da tausayi da rashin tsoron Allah, musamman yadda suke jingina wa Allah abin da su suke ƙyama a jingina musu, sannan su binne abin da suka haifa da rai wai don tana ‘ya mace.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai waɗanda ba su yi imani da ranar lahira ba su ne masu mummunar siffa, don su ne suke da siffar buƙatuwa zuwa ga ‘ya’ya sannan ga kafirci da jahilci tare da su. Amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi mai cikakkun siffofi ne na kamala maɗaukaka da cikakkiyar wadata da ilimi. Shi ne mabuwayi a mulkinsa, babu wanda zai iya rinjayar sa, mai hikima cikin halittarsa da tsarinsa da shari’arsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yalwar haƙurin Allah da rahamarsa ga bayinsa. Yana saurara wa masu laifi ba ya gaggauto musu da azaba domin ya ba su damar tuba da komawa gare shi.

2. Mummunan tasirin zunubban ‘yan’adam a duniya ba ya taƙaita a kansu su kaɗai, yakan shafi har dabbobi da suke tafiya a bayan ƙasa.

3. Babban aikin Manzon Allah (ﷺ) shi ne bayanin abin da ya zo a cikin Alƙur’ani da kuma bayanin abin da mabiya wasu addinai suka yi saɓani a kansa na aƙidu da hukunce-hukunce, domin hujjar Allah ta tabbata a kan bayinsa.

4. Sunnar Annabi (ﷺ) ita ce take bayanin abin da ya zo a Alƙur’ani na aƙida da hukunce-hukunce.

5. Alƙur’ani shiriya ne da rahama ga muminai kaɗai, domin su ne suka yi imani da shi suka gaskata duk abin da ya zo a cikinsa, don haka su kaɗai ne za su amfana da shiriyarsa da rahamarsa.

Suratun Nahl (61-64)

وَلَوْ يُؤَاخِذُ ٱللَّهُ ٱلنَّاسَ بِظُلْمِهِم مَّا تَرَكَ عَلَيْهَا مِن دَآبَّةٍ وَلَٰكِن يُؤَخِّرُهُمْ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى ۖ فَإِذَا جَآءَ أَجَلُهُمْ لَا يَسْتَخِرُونَ سَاعَةً وَلَا يَسْتَقْدِمُونَ ﴿٦١﴾ وَيَجْعَلُونَ لِلَّهِ مَا يَكْرَهُونَ ۖ وَتَصِفُ أَلْسِنَتُهُمُ ٱلْكَذِبَ أَنَّ لَهُمُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ لَا جَرَمَ أَنَّ لَهُمُ ٱلنَّارَ وَأَنَّهُم مُّفْرَطُونَ ﴿٦٢﴾ تَٱللَّهِ لَقَدْ أَرْسَلْنَآ إِلَىٰٓ أُمَمٍ مِّن قَبْلِكَ فَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ أَعْمَٰلَهُمْ فَهُوَ وَلِيُّهُمُ ٱلْيَوْمَ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٦٣﴾ وَمَآ أَنزَلْنَا عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّا لِتُبَيِّنَ لَهُمُ ٱلَّذِى ٱخْتَلَفُوا۟ فِيهِ ۙ وَهُدًى وَرَحْمَةً لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٦٤﴾

61. Da kuwa Allah Yana kama mutane da laifukansu ne to da bai bar wata dabba (mai tafiya) a bayanta ba (wato ƙasa), sai dai kuma Yana saurara musu ne har zuwa wani lokaci ƙayyadajje. To idan ajalinsu ya zo ba za su jinkirta daidai da sa’a guda ba, kuma ba za su gabata ba.

62. Suna kuma sanya wa Allah abin da suke ƙi, kuma harsunansu suna bayanin ƙaryar cewa, suna da mafi kyan sakamako; ba shakka, lalle suna da (sakamakon) wuta, kuma haƙiƙa su waɗanda za a bar su ne (cikinta har abada).

63. Wallahi haƙiƙa Mun aiko (manzanni) zuwa ga al'ummun da suke gabaninka, sai Shaiɗan ya ƙawata musu ayyukansu, kuma shi ne majiɓincin al’amuransu a yau, kuma suna da azaba mai raɗaɗi.

64. Kuma ba Mu saukar maka da Littafi ba sai don ka yi musu bayanin abin da suka yi saɓani game da shi, kuma shiriya ne da rahama ga mutanen da suke yin imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin yawan rahamarsa da haƙurinsa ga bayinsa masu yawan aikata laifuffuka. Ya nuna cewa, da a ce zai kama mutane da laifuffukansu na zalunci da kafirci

to da bai bar wani ɗan'adam ko wata dabba suna tafiya a bayan ƙasa ba, da tuni ya hallaka su gaba ɗaya. To amma yana haƙuri, yana saurara musu zuwa wani lokaci da ya ƙayyade musu, watau ranar alƙiyama, don haka su shiga taitayinsu tun kafin ajalinsu ya zo musu, domin idan har ajalinsu ya zo to ba za a saurara musu ba daidai da sa'a ɗaya, ba kuma za a gabato musu ba ko da ɗan lokaci ne ƙanƙani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wani ɓangare na zaluncinsu, watau jingina wa Allah 'ya'ya mata da zaluntar su da suke yi idan su sun same su. Ya bayyana cewa, suna jingina wa Allah abin da su ba sa so, sannan kuma harsunansu suna furta wata babbar ƙarya cewa, wai lalle su a ranar alƙiyama suna da sakamako mafi kyau a wurin Allah, watau Aljanna, idan har da gaske ne za a tashe su bayan mutuwa, domin su ba su ma yarda da alƙiyama ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa, tabbas suna da sakamakon wuta a lahira, kuma idan an jefa su cikinta za a ƙyale su ne har abada babu ranar fita.
Sai kuma ya lallashi Manzonsa (ﷺ) game da ƙaryata shi da kafirai suke yi, da cewa, ba shi ne farkon manzo da kafirai suka ƙaryata ba, Allah ya rantse masa da Zatinsa cewa, ya aika wa al'ummun da suka gabata manzanni don su kirawo su zuwa ga Tauhidi, sai Shaiɗan ya ƙawata musu munanan ayyukansu na shirka da kafirci da saɓon Allah, sai suka ƙaryata manzannin da aka aiko musu, suka ci gaba da riƙe abin da suke kai wanda Shaiɗan ya ƙawata musu, don haka ya zama shi ne majiɓincinsu a nan duniya, suka yi masa biyayya sau da ƙafa. To a lahira sai su nemi taimakonsa ya taimaka musu, domin suna da azaba mai raɗaɗi saboda bijire wa Allah da manzanninsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabi (ﷺ) dalilin da ya sanya ya saukar masa da Alƙur'ani, wato don ya bayyana wa mutane abin da suka yi saɓani a kansa na Tauhidi da tashin alƙiyama da hukunce-hukuncen shari'a, kuma Alƙur'ani ya zamanto shiriya da rahama ga muminai, domin su ne masu amfanuwa da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abubakar Al-Warraƙ (Allah ya ƙara masa yarda) yana cewa,: "Izina a game da dabbobi ita ce: Horewarsu ga masu su, da biyayyarsu gare su, da bijirewar ɗan'adam ga Ubangijinsa da saɓa masa a kan komai. Yana daga cikin mafi girman darasi ka ga marar laifi ya goyo mai laifi." [Dubi, Al-Kurɗubi, Juzu'i na 12, shafi na 350].

2. Fitowar tataccen nono fari ƙal mai daɗin kwankwaɗa daga ciyawar da dabba za ta ci ta shiga tumbinta sannan ta zama jini jawur, daga nan wannan jinin ya rikiɗe ya koma nono fari tatacce mai daɗi, lalle wannan babban abu ne da ke nuna cikar Kudurar Allah a kan komai da Kaɗaitakarsa a mulkinsa da buwayarsa (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. A cikin rayuwar ƙudan zuma akwai abubuwan ban al'ajabi masu nuni ga cikakkiyar Kudurar Allah da hikimarsa. Kudan zuma suna rayuwa ne ƙungiya-ƙungiya, kowace ƙungiya tana da mahallinta daban da na 'yar'uwarta, sannan a cikin kowace ƙungiya akwai sarauniya guda ɗaya duk ta ɗara sauran girma, ita ce mai ba da umarni ga sauran ƙudan zumar. Sannan akwai maza a cikin kowace ƙungiya da sun kai kimanin su ɗari huɗu zuwa ɗari biyar. Sannan akwai masu hidima waɗanda adadinsu yakan kai kimanin dubu sha biyar. Haka suke rayuwa cikin kyakkyawan tsari. Ita sarauniya ita ce take saka ƙwai, don haka ita ce uwa, su kuma sauran mazan aikinsu shi ne yi mata barbara, sauran 'yan aiki kuma su yi ta hidima ga sarauniya da mazanta. Za su yi ta kai-kawo a duk tsawon rana suna tsotso furanni daga gonaki suna mayar da su ruwan zuma, sauran 'yan wannan ƙungiya suna shan sa, manyansu da ƙanana, suna furzar da wani abu mai danƙo wanda da shi suke gina kasakensu masu kwami shida-shida, a nan ne suke ɓoye zumar daga baya 'yan'adam su dinga ɗiba suna sha suna kuma amfani iri-iri da ita.

4. Yana daga cikin ayoyin Allah a game da zuma kasancewarta magani ga cututtuka iri-iri. Masana ilimin kimiyyar magunguna sun ambaci cewa, zuma ta ƙunshi kimanin kaso 25 zuwa 40 na sinadarin (glucose) mai ƙara wa jiki kuzari. Sinadarin da yake cikin zuma ya fi na cikin kowane irin abinci, kuma yana amfani wajen magance cututtuka da dama, ana kuma amfani da shi ta hanyoyi daban-daban na kimiyyar likitancin zamani.

Suratun Nahl (65-69)

وَٱللَّهُ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَحۡيَا بِهِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَآۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّقَوۡمٖ يَسۡمَعُونَ ٦٥ وَإِنَّ لَكُمۡ فِي ٱلۡأَنۡعَٰمِ لَعِبۡرَةٗۖ نُّسۡقِيكُم مِّمَّا فِي بُطُونِهِۦ مِنۢ بَيۡنِ فَرۡثٖ وَدَمٖ لَّبَنًا خَالِصٗا سَآئِغٗا لِّلشَّٰرِبِينَ ٦٦ وَمِن ثَمَرَٰتِ ٱلنَّخِيلِ وَٱلۡأَعۡنَٰبِ تَتَّخِذُونَ مِنۡهُ سَكَرٗا وَرِزۡقًا حَسَنًاۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ٦٧ وَأَوۡحَىٰ رَبُّكَ إِلَى ٱلنَّحۡلِ أَنِ ٱتَّخِذِي مِنَ ٱلۡجِبَالِ بُيُوتٗا وَمِنَ ٱلشَّجَرِ وَمِمَّا يَعۡرِشُونَ ٦٨ ثُمَّ كُلِي مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ فَٱسۡلُكِي سُبُلَ رَبِّكِ ذُلُلٗاۚ يَخۡرُجُ مِنۢ بُطُونِهَا شَرَابٞ مُّخۡتَلِفٌ أَلۡوَٰنُهُۥ فِيهِ شِفَآءٞ لِّلنَّاسِۗ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ ٦٩

65. Allah kuma Ya saukar da ruwa daga sama, sai Ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta. Lalle a game da wannan akwai aya ga mutanen da suke ji.

66. Lalle kuma kuna da wata izina a game da dabbobin ni'ima; Muna shayar da ku da abin da yake cikin cikkunansu (mai fitowa) ta tsakankanin uwar hanji da jinni; nono tatacce mai daɗin kwankwaɗa ga masu sha.

67. Daga kuma ‘ya’yan dabinai da na inabai kuna yin giya da shi, da kuma arziki mai kyau. Lalle a game da wannan akwai aya ga mutanen da suke hankalta.

68. Ubangijinka kuma Ya kimsa wa ƙudan zuma cewa,: “Ki gina gidaje a duwatsu da kan bishiyoyi da kuma rufin da (mutane) suke yi”

69. “Sannan kuma ki ci daga kowanne ‘ya’yan itace, kuma ki shiga hanyoyin Ubangijinki horarru (gare ki).” Abin sha mai launi daban-daban yana fitowa daga cikin cikinta; a cikinsa (kuma) da akwai waraka ga mutane. Lalle a game da wannan akwai aya ga mutane masu tunani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ambaton dalilai na tabbatar da Kaɗaitakarsa wajen bauta. Ya bayyana cewa, shi ne ya saukar da ruwan sama, ya raya ƙasa da shi bayan da ta bushe ta ƙeƙashe, ya fitar da tsirrai daga cikinta. Don haka duk wanda ya yi wannan aiki mai iko ne kan ya sake tayar da matattu bayan mutuwarsu. Lalle cikin wannan akwai aya ga mutanen da suke sauraron wa’azi su fahimci dalilin Kaɗaita Allah da bauta da rashin dacewar a bauta wa wani ba shi ba.
Sannan ya ambaci wata hujjar ita ma mai nuna cikakkiyar Kudirar Ubangiji da dacewar a bauta masa shi kaɗai, ya tabbatar da cewa, game da dabbobin ni’ima, watau raƙuma da shanu da tumaki da awaki, akwai wata ƙaƙƙarfar hujja ga mutane da take ƙara tabbatar musu da Kaɗaitakar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai da cikar Kudurarsa. Waɗannan dabbobi mutane na amfana da su ta hanyoyi daban-daban; su ci namansu su sha nononsu su ɗora wa wasu kaya ko su hau.
Ya bayyana cewa, wani ma abin mamakin da ɗan’adam yake gani a kullum wanda kuma yake cike da nuna Kudurar Allah shi ne, tacaccen nono da yake fitowa daga waɗannan dabbobi ta tsakanin abin da yake cikin uwar hanji da jinin da ke gudana a jikinsu, sai wannan nonon ya fito tatacce fari ƙal mai daɗin kwankwaɗa ga masu shan sa.

Bayan wannan kuma ga wasu hujjojin da ke tattare da tsirrai na ‘ya’yan dabino da inabi wanda Allah ya arzuta mutane da shi, har ma wasu suke yin abin sa maye da shi suna sha, wanda kuwa yin hakan ba abu ne mai kyau ba, sannan kuma suna yin abin arziki mai kyau da shi.
Wannan ayar ta sauka kafin a haramta shan giya. Daga baya Allah ya haramta shan duk wani abu mai gusar da hankali kamar yadda ya zo cikin *Suratul Ma’ida*, aya ta 90-91.Sannan ya bayyana cewa, lalle cikin wannan aiki na Allah akwai aya ga mutane masu hankalta su fahimci cikakken ikon Allah.
Sai kuma ya ci gaba da bayyana wata hujjar ita ma mai cike da al’ajabi wadda ta isa ta nuna Kaɗaitakar Allah Ta’ala, ita ce yadda ya kimsa wa ƙudan zuma cewa, su nufi cikin tsaunuka da bishiyoyi su yi gidajensu a can. Hakanan su yi a cikin amyoyi da mutane suke gina masu su rufa masu su. Sannan ya kimsa masu su je su samu ‘ya’yan itatuwa da furanni da suke sha’awa su ci, su bi hanyoyin da Allah ya hore musu bin su har su ƙomo gidansu ba tare da sun yi ɓatan kai ba ko wani ya shiga wanda ba nasa ba. Sannan daga cikin cikinsu ne zuma iri-iri za ta riƙa fita saboda bambancin ganyaye da furanni da suka tsotsa. Allah ya bayyana cewa, a cikin wannan zumar akwai magani ga mutane mai warkar da cututtuka da dama. Wannan lalle babbar hujja ce mai nuna cikakkiyar Kudurar Allah da rahamarsa ga bayinsa, amma ba kowa ne yake gane haka ba sai mutane masu tunani.

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Wani mutum ya zo wajen Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ɗan’uwana yana fama da gudawa.” Sai Annabi (ﷺ) ya ce masa: “Je ka ba shi zuma ya sha.” Sai ya je ya ba shi zuma ya sha, amma sai ga shi kuma ya dawo ya ce: “Ya Manzon Allah, na ba shi zuma ya sha, amma gudawarsa ta ƙaru.” Manzon Allah (ﷺ) ya sake ce masa: “Je ka ka ba shi zuma ya sha.” Ya tafi ya ba shi zuma ya sha, sai kuma ga shi ya sake dawowa ya ce: “Ya Manzon Allah, na ba shi ya sha amma kuma gudawarsa ta daɗa ƙaruwa.” Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah ya yi gaskiya, cikin ɗan’uwanka kuma ya yi ƙarya, ka sake ƙomawa ka shayar da shi zuma.” Ya sake ƙomawa ya ba shi zuma ya sha sai ya warke.” [Bukhari #5684 da Muslim #2217].

Wasu daga cikin masana magunguna sun ce abin da ya faru game da wannan mutum mai gudawa, cikinsa ne ya kume, to da aka ba shi zuma ya sha sai zumar ta sanya cikin ya saki, domin zuma tana da ɗabi’ar zafi, to sai gudawarsa ta ƙaru, to sai ɗan’uwansa ya zaci ko ta cutar da shi ne, alhalin hakan shi ne maslaha ga ɗan’uwansa. Da ya sake shayar da shi a karo na biyu sai cikin ya ƙara saki, sai gudawar ita ma ta ƙaru, to hakanan da ya sake ba shi ya ci gaba da gudawar har sai da duk abincin da ya ci ya ɓata masa cikin nasa har ya kume ya fita daga jikinsa sai ya samu lafiya.

An karɓo daga Nana A’isha, Allah ya yarda da ita ta ce: “Manzon Allah (ﷺ) yana sha’awar abu mai zaƙi da kuma zuma.” [Bukhari#5431 da Muslim#1474].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Akwai magani cikin abubuwa uku: Jarfar ƙaho da shan zuma da lalas da wuta, amma ina hana al’ummata yin lalas.” [Bukhari #5680].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai fifita wanda ya ga dama wajen arziki, wayo ko ƙarfin mutum ba shi yake ba shi ba. Don haka sai ka ga mutum mai cikakken hankali da wayo da ƙarfi da yawan kazar-kazar wajen neman abin duniya, amma sai ka ga ya rasa samun wani abin a zo a gani. Kuma ka ga wani marar ilimi mai ƙarancin hankali da wayo Allah ya buɗe masa ƙofofin samu masu yawa. Ban da Allah babu mai iya yin haka.

2. Wadata da talauci abubuwa ne da Allah ya hukunta wanzuwarsu cikin rayuwar al'umma, saboda haka jahilci ne da rashin sanin hikimomin Ubangiji suke sa wasu su rika tutiya suna karyar cewa, sun mallaki wani tsari na siyasa ko na gudanarwa wanda zai kawar wa mutane talauci. Wannan tatsuniya ce ta 'yan gurguzu wadda ba a taba ganin ta auku ba a cikin kowace, al'umma saboda ta ci karo da sunnar Allah (Mai tsarki da daukaka).

3. Duk wanda ya fahimci Allah ne mai fifitawa wajen bayar da arziki to zai nisanci hassada ga wanda Allah ya yi masa wani arziki.

4. Aure da haihuwar 'ya'ya da jikoki wata ni'ima ce babba daga ni'imomin Allah da ya wajaba bayi su yi masa godiya a kai su kiyaye dokokinsa da ya gitta musu.

5. Raunin dan'adam tun daga lokacin haihuwarsa har zuwa lokacin tsufansa wani kakkarfan dalili ne mai nuna gajiyawar bawa da nakasarsa da tsananin bukatuwarsa zuwa ga Allah mai cikakkiyar Kudura wanda babu wata siffa tasa da take canzawa har abada.

Suratun Nahl (70-72)

وَٱللَّهُ خَلَقَكُمۡ ثُمَّ يَتَوَفَّىٰكُمۡۚ وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ إِلَىٰٓ أَرۡذَلِ ٱلۡعُمُرِ لِكَيۡ لَا يَعۡلَمَ بَعۡدَ عِلۡمٖ شَيۡـًٔاۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٞ قَدِيرٞ ٧٠ وَٱللَّهُ فَضَّلَ بَعۡضَكُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖ فِي ٱلرِّزۡقِۚ فَمَا ٱلَّذِينَ فُضِّلُواْ بِرَآدِّي رِزۡقِهِمۡ عَلَىٰ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُمۡ فَهُمۡ فِيهِ سَوَآءٌۚ أَفَبِنِعۡمَةِ ٱللَّهِ يَجۡحَدُونَ ٧١ وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ أَزۡوَٰجٗا وَجَعَلَ لَكُم مِّنۡ أَزۡوَٰجِكُم بَنِينَ وَحَفَدَةٗ وَرَزَقَكُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِۚ أَفَبِٱلۡبَٰطِلِ يُؤۡمِنُونَ وَبِنِعۡمَتِ ٱللَّهِ هُمۡ يَكۡفُرُونَ ٧٢

70. Kuma Allah ne Ya halicce ku, sannan kuma Shi zai kashe ku. Daga cikinku akwai wanda zai zama tsoho tukuf don kada ya san komai bayan (da can yana da) sani. Lalle Allah Masani ne, Mai iko.

71. Allah kuma Ya fifita sashenku a kan wani sashi a arziki. Wadanda aka fifita din ba za su ba da arzikin nasu ga bayinsu ba don su zama daidai a cikinsa. Shin da ni'imar Allah ne suke jayayya?

72. Allah kuma Ya sanya muku matan aure daga jinsinku, Ya kuma sanya muku 'ya'yaye da jikoki daga matayen naku, Ya kuma arzuta ku da abubuwa tsarkaka. Yanzu da karya suke yin imani kuma suke kafirce wa ni'imar Allah?

A wadannan ayoyi Allah (Mai tsarki da daukaka) ya bayyana matakai daban-daban da mutum yakan keto a rayuwarsa da yawan shekarunsa a duniya. Ya bayyana cewa, shi ne ya halicci mutane bayan babu su, sannan idan lokacin mutuwarsu ya zo shi zai karbi rayukansu. Ya kayyade wa kowa ajalinsa. Daga cikin mutane akwai wanda yake yin tsawon rai har ya tsufa tukuf, gabobinsa su yi rauni hankalinsa ya rika ja da baya har ya sake dawowa kamar karamin yaro, ba ya iya fahimtar komai daga irin abubuwan da yake fahimta lokacin ganiyar kuruciyarsa da karfinsa, watau ya koma mai yawan mantuwa. Lalle Allah masanin komai ne, shi kuma yake da sanin hikimar yin halittar dan'adam a irin wadannan matakai. Kuma mai iko ne a kan komai babu abin da yake gagarar sa.

An karbo daga Anas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance yana addu'a yana cewa,: "Ya Allah, ina rokon ka ka tsare ni daga rowa da kasala da tsufa da zama tsoho takwarkwasasshe da azabar kabari da fitinar Dujal da fitinar rayuwa da mutuwa." [Bukhari #4707].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci fifikon arzuka da ke tsakanin mutane wanda shi ma aikinsa ne shi kaɗai, babu mai tarayya da shi a cikinsa. Allah ya halicci mutane, wasu ya ba su arziki mai yawa, wasu talakawa, wasu sarakuna, wasu kuma waɗanda ake mulka ne. Waɗanda Allah ya ba su arziki ba za su yarda su damƙa wannan arzikin ga bayinsu ba su zama sun yi tarayya da su daidai-wa-daida. To idan haka ne me ya sa su kafirai suka yarda su sanya wa Allah kishiyoyi daga cikin bayinsa, amma su ba su amince bayinsu su yi tarayya da su cikin dukiyoyinsu ba? Wane irin zalunci ne wannan? Wanne butulci ne ya kai wannan?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu ni'imomi na musamman da ya yi wa bayinsa saboda biya musu duk buƙatunsu na rayuwa, inda ya ce, ya halitta wa mutane matan aure daga jinsinsu don su sami nutsuwa da su, sannan ya ba su 'ya'ya da jikoki daga matayen, ya kuma hore musu arzikin abubuwan da za su ci su sha masu daɗi su da iyalansu. To yanzu duk da irin waɗannan ni'imomi masu yawa da ya yi musu sai kuma su butulce masa, su riƙa yin imani da ƙarya, watau gumakansu da cewa suna amfanarwa suna kuma cutarwa, har ma wai za su cece su a wurin Allah?

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "A ranar alƙiyama Allah zai goranta wa bawa ya ce masa: 'Wane, ashe ba ni ne na karrama ka ba, na ba ka shugabanci; na ba ka aure; na hore maka dawakai da raƙuma; na ƙyale ka kana karɓe ɗaya bisa huɗu na dukiyar ganima?'" [Muslim #2968].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne kaɗai yake da ilimin gaibin sammai da ƙasa.

2. Misalai biyu da Allah ya bayar a cikin waɗannan ayoyi suna nuna ɓatan basira da mushirikai suke ciki na bautar gumaka. Domin abin bauta na gaskiya dole ne ya zamanto mai cikakken mulki mai kuma ikon sarrafa komai yadda ya ga dama, ya amfanar da wanda yake bautar sa; ya yi umarni da alheri ya hana mummuna tare da adalci.

3. Bawan da wani ya mallaka ba shi da haƙƙin mallakar komai sai da izinin mai gidansa, domin shi da abin da zai samu duka na mai gidansa ne.

Suratun Nahl (73-77)
وَيَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَمۡلِكُ لَهُمۡ رِزۡقٗا مِّنَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ شَيۡـٔٗا وَلَا يَسۡتَطِيعُونَ ٧٣ فَلَا تَضۡرِبُواْ لِلَّهِ ٱلۡأَمۡثَالَۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ وَأَنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ ٧٤ ۞ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا عَبۡدٗا مَّمۡلُوكٗا لَّا يَقۡدِرُ عَلَىٰ شَيۡءٖ وَمَن رَّزَقۡنَٰهُ مِنَّا رِزۡقٗا حَسَنٗا فَهُوَ يُنفِقُ مِنۡهُ سِرّٗا وَجَهۡرًاۖ هَلۡ يَسۡتَوُۥنَۚ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِۚ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٧٥ وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا رَّجُلَيۡنِ أَحَدُهُمَآ أَبۡكَمُ لَا يَقۡدِرُ عَلَىٰ شَيۡءٖ وَهُوَ كَلٌّ عَلَىٰ مَوۡلَىٰهُ أَيۡنَمَا يُوَجِّههُّ لَا يَأۡتِ بِخَيۡرٍ هَلۡ يَسۡتَوِي هُوَ وَمَن يَأۡمُرُ بِٱلۡعَدۡلِ وَهُوَ عَلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٧٦ وَلِلَّهِ غَيۡبُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَمَآ أَمۡرُ ٱلسَّاعَةِ إِلَّا كَلَمۡحِ ٱلۡبَصَرِ أَوۡ هُوَ أَقۡرَبُۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٧٧

73. Suna kuma bauta wa wasu ba Allah ba, waɗanda ba sa mallakar musu wani arziki a sammai da ƙasa, ba za kuma su iya ba.

74. Kada kuma ku sanya wa Allah abokan tarayya. Lalle Allah Yana sane, ku ne ba ku sani ba.

75. Allah kuma Ya ba da misali da bawan da aka mallaka, ba shi da iko a kan komai, da kuma wanda Muka bai wa arziki nagari daga gare Mu, to shi kuma yana ciyarwa daga shi (arzikin) a ɓoye da kuma sarari; yanzu

za su yi daidai? (Ai ba za su yi daidai ba). To godiya ta tabbata ga Allah. A'a, yawancinsu dai ba su san (haka) ba ne.

76. Allah kuma Ya ba da wani misali da mutum biyu, ɗayansu bebe ne ba ya iya yin komai, kuma ya zama nauyi a kan mai gidansa, duk inda ya fuskantar da shi ba zai zo da wani alheri ba. Yanzu shi zai yi daidai da wanda yake umarni da adalci kuma yana bisa tafarki madaidaici?

77. Kuma Allah ne Masanin gaibu na sammai da ƙasa. Al'amarin alƙiyama kuma ba komai ba ne face kamar ƙiftawar ido ko kuma ya fi haka kusa. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana ƙarfafan hujjojin da ke nuna ɓacin aƙidar bautar wanin Allah, inda ya ce, mushirikai suna bautar wasu gumaka ba Allah ba, waɗanda ba su mallaki wani arzuki na sama ko na ƙasa ba da za su ba su, kuma ma ba za su iya hakan ba, saboda daskararrun abubuwa ne, sassaƙaƙƙun itatuwa ne ko kwaɓaɓɓiyar laka babu rai tare da su. Don haka ya yi wa mutane kashedi da cewa, su guji danganta Allah da wasu misalai na gumaka waɗanda ba su da ikon amfanarwa ko cutarwa. Allah ba shi da tamka ballantana a haɗa shi da shi wajen bauta. Allah shi ne ya san haƙiƙanin siffofinsa na kamala da isa; su mushirikai ba su san komai ba, shi ya sa suke aukawa cikin shirka suna kwatanta Allah da gumakansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake bayyana wani misali wanda yake ƙara fito da ɓacin aƙidar bautar wanin Allah da wautar da ke tare da masu yinta. Ya ba da misali na wasu mutane su biyu, ɗayansu bawa ne gajiyayye babu abin da yake iya yi da kansa sai abin da aka sa shi; ɗayan kuwa ɗa ne mai cikakken iko, Allah ya wadata shi da dukiya ta halal yana juya ta yadda ya ga dama, yana yi wa mutane kyauta da ita a sarari da ɓoye. Yanzu ta yaya za a daidaita wannan da wancan bawa na farko? Babu shakka ba za su zama ɗaya ba, duk kuwa da kasancewarsu mutane ne. To idan ya kasance su biyun an halicce su ne, amma ba za su daidaita ba, to ta yaya kafirai za su daidaita wani mahaluƙi da Allah mahalicci mai kowa mai komai? Don haka ne Allah ya yi wa kansa kirari da yabo, ya kuma ya tabbatar da cewa, yawancin mushirikai ba su san haƙiƙanin girman Allah ba ne, da a ce sun sani da sun guji yi masa shirka.
Sai kuma ya bayar da misali na biyu domin ya ƙara fito musu da lamarin sararai don su fahimta, inda ya kawo musu misalin wasu mutane su biyu, ɗayansu bebe ne ba ya iya magana ba ya jin komai ba ya fahimtar komai, ba zai iya amfanar kansa ba ballantana ya amfanar da wani. Ya zama kaya mai nauyi a wuyan wanda yake ciyar da shi yake ɗaukar nauyin rayuwarsa. Duk inda ya tura shi don ya samo wani alheri ba zai dawo masa da komai ba, haka zai dawo ziƙau kamar yadda ya tafi. Ɗayan kuwa mutum ne lafiyayye, yana ji yana gani yana magana, yana iya amfanar kansa har ma ya amfanar da wasu; ga shi kuma duk maganganunsa da ayyukansa na adalci ne suna kuma kan hanya miƙaƙƙiya. To shin yanzu za su iya daidaita waɗannan mutane guda biyu? To kamar yadda ba za su daidaita ba, hakanan ma duk wanda aka bauta wa ba Allah ba wanda bai san wani abin amfani ga kansa ba, ba zai iya yi wa kansa komai ba sai abin da Allah ya nufe shi da shi, ta yaya zai zama daidai da Allah mai cikakkun siffofi na kamala, mai iko a kan komai, wanda ba ya faɗar wata magana sai gaskiya, ba ya aikata wani aiki sai wanda za a gode masa a kansa?
Sannan ya ƙara bayyana siffarsa da cewa, shi ne kaɗai ya san abin da yake ɓoye a sammai da ƙasa, babu kuma wani da yake tarayya da shi a sanin hakan. Daga cikin abubuwan da suke ɓoye babu wanda ya san lokacin zuwansu akwai ranar alƙiyama, wadda al'amarinta a wurinsa duk lokacin da ya nufi zuwanta kamar ƙiftawar ido ne, ko ma ya fi haka kusa, domin da ya umarce ta ta kasance to za ta kasance. Lalle shi mai iko ne a kan komai babu abin da yake buwayarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daga cikin manya-manyan ni'imomin Allah masu nuna cikakkiyar Kudurarsa, shi ne yadda ya halicci mutane a cikin cikunan iyayensu mata a lokacin babu abin da suka sani. Sannan ya samar musu kafofin da

za su sami ilimi daga gare su, su ne ji da gani da zukata; ta waɗannan hanyoyi ne suke riskar abubuwa su fahimce su.

2. Duk da cewa, Allah ne ya halicci duka sassan jikin ɗan'adam amma sai ya ware waɗannan ukun da ambato, watau ji da gani da zuciya, saboda ƙara fito da darajarsu da falalarsu, kuma saboda su ne mabuɗin kowane ilimi, babu wani ilimi da ɗan'adam zai kai gare shi sai ta hanyar ɗaya daga cikin waɗannan kafofi uku.

3. Godiya ga Allah tana tabbata ne ta hanyar amfani da waɗannan gaɓoɓi a inda ya dace da biyayya ga Allah. Duk wanda ya yi amfani da wata gaɓa tasa a kan abin da Allah ya hana to wannan ya nuna butulcinsa gare shi bai gode wa ni'imominsa ba.

Suratun Nahl (78-79)
وَٱللَّهُ أَخۡرَجَكُم مِّنۢ بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ شَيۡـٔٗا وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَٱلۡأَفۡـِٔدَةَ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ٧٨ أَلَمۡ يَرَوۡاْ إِلَى ٱلطَّيۡرِ مُسَخَّرَٰتٖ فِي جَوِّ ٱلسَّمَآءِ مَا يُمۡسِكُهُنَّ إِلَّا ٱللَّهُۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ٧٩

78. Allah ne kuma Ya fito da ku daga cikkunan iyayenku, ba ku san komai ba, Ya kuma sanya muku ji da gani da kuma zukata don ku gode masa.

79. Yanzu ba sa ganin tsuntsaye da aka lamunce wa (tashi) a sararin sama, ba mai riƙe su sai Allah? Lalle a game da wannan akwai ayoyi ga mutane masu yin imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da jan hankali a kan a yi la'akari da wasu ayoyi masu nuna cikar ikonsa, da cewa, shi ne ya fito da mutane suna jarirai daga cikkunan iyayensu mata, suka haifo su ba su san komai ba, amma Allah ya samar musu ji da gani ya saka musu zukata, domin su riƙa jin abin da ake faɗa, su ga abubuwa yadda suke, su kuma fahimci yadda ya kamata su rayu, ya yi musu waɗannan ni'imomi ne duka domin su gode masa ta hanyar bin umarninsa da guje wa haninsa da neman yardarsa.
Sannan kuma ya ci gaba da jawo hankalin mushirikai masu bautar wasu gumaka ba Allah ba da cewa, su duba su ga tsuntsaye a sama waɗanda aka hore wa tashi cikin iska saboda fiffike da Allah ya ba su, ya kimsa musu yadda za su riƙa rufe su suna buɗewa babu wani abu a sama da yake riƙe da su, kuma babu wani abu a ƙasa da yake ɗauke da su, babu mai riƙe su sai Allah mai cikakken iko. To lalle a cikin wannan aiki na Ubangiji akwai babbar aya ga mutanen da suka yi imani da Allah, domin su ne masu amfanuwa da irin wannan faɗakarwar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kimsa wa ɗan'adam yadda zai tanadar wa da kansa gidan zama domin samun hutu da tsare kansa daga duk wasu abubuwa masu cutar da shi, ko kare kansa daga zafin rana da iska da ƙura; wannan wata babbar ni'ima ce gare shi wadda idan da zai dube ta ita kaɗai ta isa ta sa shi godiya ga Allah da miƙa wuya gare shi.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya taƙaita ambaton zafi kaɗai a cikin wannan aya ta 81 domin yawancin garuruwan Larabawa suna da yanayin tsananin zafi ne, don haka buƙatarsu ta fi ƙarfi wajen neman abin da zai kare su daga tsananin zafi. Sannan idan sun sami abin zai kare su daga zafi mai tsanani ɗin, to ɗan abin da zai yi saura na zafin ya isa ya kare su daga sanyi.

3. Babban aikin da yake kan Annabi (ﷺ) shi ne isar da saƙo, shiriya kuma tana hannun Allah ne.

4. Yawancin kafiran da suka ƙaryata Annabi (ﷺ) sun san yana da gaskiya, to amma sun ƙaryata shi ne saboda girman kai da hassada.

5. Duk wanda ya yi amfani da ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi cikin abin da Allah ya haramta, to bai gode wa Allah ni'imominsa ba, ya tabbata babban butulu.

6. Ayoyin sun nuna halaccin amfani da gashin tumaki da na raƙuma da na awaki.

7. Yawaitar ni'imomin Allah ga bayinsa suna daga cikin abubuwa da suke wajabta musu yawaita godiya ga Allah da yabo gare shi da guje wa butulce masa.

Suratun Nahl (80-83)

وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّنۢ بُيُوتِكُمۡ سَكَنٗا وَجَعَلَ لَكُم مِّن جُلُودِ ٱلۡأَنۡعَٰمِ بُيُوتٗا تَسۡتَخِفُّونَهَا يَوۡمَ ظَعۡنِكُمۡ وَيَوۡمَ إِقَامَتِكُمۡ وَمِنۡ أَصۡوَافِهَا وَأَوۡبَارِهَا وَأَشۡعَارِهَآ أَثَٰثٗا وَمَتَٰعًا إِلَىٰ حِينٖ ٨٠ وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّمَّا خَلَقَ ظِلَٰلٗا وَجَعَلَ لَكُم مِّنَ ٱلۡجِبَالِ أَكۡنَٰنٗا وَجَعَلَ لَكُمۡ سَرَٰبِيلَ تَقِيكُمُ ٱلۡحَرَّ وَسَرَٰبِيلَ تَقِيكُم بَأۡسَكُمۡۚ كَذَٰلِكَ يُتِمُّ نِعۡمَتَهُۥ عَلَيۡكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تُسۡلِمُونَ ٨١ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا عَلَيۡكَ ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٨٢ يَعۡرِفُونَ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ ثُمَّ يُنكِرُونَهَا وَأَكۡثَرُهُمُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ٨٣

80. Allah ne kuma Ya sanya muku gidajienku wuraren hutawarku, Ya kuma sanya muku gidaje daga fatun dabbobin ni'ima, kuna ɗaukar su ba nauyi a ranar tafiyarku da ranar saukarku. Daga kuma gashin (tumaki) da gashin raƙuma da gashin (awaki, Ya sanya muku) kayan shimfiɗa da kuma (kayan) jin daɗi zuwa wani ɗan lokaci.

81. Kuma Allah ne Ya sanya muku inuwoyi daga abin da Ya halitta, Ya kuma sanya muku ɗakuna daga duwatsu, Ya kuma sanya muku riguna da suke kare ku daga zafi, da kuma riguna (na sulke) da suke kare ku (daga makamai) a fagen daga. Kamar haka ne Yake cika muku ni'imarsa don ku miƙa wuya.

82. To idan suka ba da baya, to kai isar da aike a fili ne kawai a kanka.

83. Suna sane da ni'imar Allah sannan sai su musanta ta, yawancinsu kuwa kafirai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana wasu ni'imominsa ga 'yan'adam a halin zaman gidansu ko halin tafiye-tafiyensu. Allah ya kimsa musu yadda za su gina gidaje na duwarwatsu ko na tubala a cikin birane domin hutawarsu. Hakanan ya nuna musu yadda za su yi gidaje na tantuna waɗanda ake yin su da fatun dabbobi kamar na raƙuma da shanu da tumaki, suna kuma iya ɗaukar su saboda rashin nauyinsu suna tafiye-tafiye da su, kamar yadda suke amfani da su a ƙauyukansu. Hakanan kuma ya nuna musu yadda za su yi amfani da gashin waɗannan dabbobi wajen saƙa kayan shimfiɗa a gidajensu da tufafin sawa da na lulluɓa, waɗanda suke morar su na ɗan lokaci.
Haka kuma yana daga cikin ni'imomin da Allah ya yi wa 'yan'adam yadda ya samar musu da inuwoyi na bishiyoyi da gine-gine da suke yi, ya samar musu da ɗakuna a jikin duwarwatsu, watau koguna da ke jikinsu suna kare su daga sanyi da iska da ƙura. Kamar yadda ya ni'imta su da samar musu tufafin sawa na auduga da kittani da ulu waɗanda suke kare su daga zafi. Hakanan ya sanya musu wasu rigunan na silke waɗanda suke amfani da su wajen yaƙe-yaƙensu don kare kai daga sara da suka.

Sai kuma ya bayyana musu cewa, kamar yadda ya tanadar musu waɗannan ni'imomi da ya ambata, to hakanan zai cika musu sauran ni'imominsa don ko sa miƙa wuya gare shi shi kaɗai su daina bautar wasu ba Allah ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa (ﷺ) tabbacin cewa, idan mushirikan nan suka bijire suka ƙi yin imani bayan duk irin waɗannan bayanai filla-filla da aka yi musu da hujjoji ƙarfafa na sarari, to kada ya damu kansa, domin shi babban aikinsa shi ne isar da saƙon Allah a bayyane, amma shiriyarsu a hannun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) take, yana shiryar da wanda ya ga ɗama daga cikinsu.
Sai kuma ya bayyana cewa, su waɗannan mushirikai masu ƙaryata Annabi (ﷺ) da abin da ya zo musu da shi na bautar Allah shi kaɗai suna yin hakan ne domin kawai girman kai da jayayya, don kuwa sun san duk waɗannan ni'imomin Allah ne da ya yi musu, amma suke musantawa, suna jingina wasunsu ga gumakansu, suna ƙaryata manzancin Annabi (ﷺ). Don haka mafi yawancinsu kafirai ne masu musunta ni'imomin Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kowane manzo shi ne mai ba da shaida a kan al'ummarsa game da abin da ta aikata kyakkyawa da mummuna. Wannan yana daga cikin cikar adalcin Allah, domin ya ɗauki shaidar da ya fi kowa gaskiya da kwatanta adalci wanda kuma ya fi sanin abin da zai bayar da shaida a kansa, shi ne Manzo.

2. Duk wanda ya bauta wa wani ba Allah ba a nan duniya, to a lahira za su yi baram-baram da shi, domin zai nesanta kansa da shi ya ƙaryata shi a gaban Ubangiji.

3. Duk wanda ya riƙi wani a duniya ba Allah ba, yana kuma kwaɗayin samun cetonsa a lahira, to zai gane cewa, ya saki reshe ne ya kama ganye, domin zai neme shi ya rasa ya ɓace masa ɓat.

4. Kafirai ma azabarsu a lahira hawa-hawa ce, ta wani ta fi ta wani; gwargwadon kafircin kowa haka Allah zai yi masa azaba, kamar yadda sakamakon muminai a Aljanna yake mataki-mataki.

5. Alƙur'ani ya ƙunshi bayanin komai na rukunan addinin Musulunci da hukunce-hukuncensa da duk abin da ya danganci buƙatar bayi. Allah ya yi bayaninsa cikakken da kalmomi masu ɗauke da bayyanannun ma'anoni babu wani ba-duhu a cikinsa. A wasu wurare ma a cikinsa yakan nanata bayanin wasu manyan mas'aloli domin buƙatar hakan kuma a fahimce su sosai. Don haka duk wanda ya bar Alƙur'ani ya tafi neman wani tsari daban na addini ko na rayuwa, to ba shi da wata hujja a gaban Allah. Hakanan duk wani tsari ba na Alƙur'ani ba ba zai iya samar wa da ɗan'adam jin daɗi a rayuwarsa ta duniya ba, ballantana kuma in an koma lahira.

Suratun Nahl (84-89)
وَيَوۡمَ نَبۡعَثُ مِن كُلِّ أُمَّةٖ شَهِيدٗا ثُمَّ لَا يُؤۡذَنُ لِلَّذِينَ كَفَرُواْ وَلَا هُمۡ يُسۡتَعۡتَبُونَ ٨٤ وَإِذَا رَءَا ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ ٱلۡعَذَابَ فَلَا يُخَفَّفُ عَنۡهُمۡ وَلَا هُمۡ
يُنظَرُونَ ٨٥ وَإِذَا رَءَا ٱلَّذِينَ أَشۡرَكُواْ شُرَكَآءَهُمۡ قَالُواْ رَبَّنَا هَٰٓؤُلَآءِ شُرَكَآؤُنَا ٱلَّذِينَ كُنَّا نَدۡعُواْ مِن دُونِكَۖ فَأَلۡقَوۡاْ إِلَيۡهِمُ ٱلۡقَوۡلَ إِنَّكُمۡ لَكَٰذِبُونَ ٨٦
وَأَلۡقَوۡاْ إِلَى ٱللَّهِ يَوۡمَئِذٍ ٱلسَّلَمَۖ وَضَلَّ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ ٨٧ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ زِدۡنَٰهُمۡ عَذَابٗا فَوۡقَ ٱلۡعَذَابِ بِمَا كَانُواْ
يُفۡسِدُونَ ٨٨ وَيَوۡمَ نَبۡعَثُ فِي كُلِّ أُمَّةٖ شَهِيدًا عَلَيۡهِم مِّنۡ أَنفُسِهِمۡۖ وَجِئۡنَا بِكَ شَهِيدًا عَلَىٰ هَٰٓؤُلَآءِۚ وَنَزَّلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ تِبۡيَٰنٗا لِّكُلِّ شَيۡءٖ
وَهُدٗى وَرَحۡمَةٗ وَبُشۡرَىٰ لِلۡمُسۡلِمِينَ ٨٩

84. Kuma (ka tuna) ranar da za Mu tayar da mai shaida daga kowacce al'umma, sannan ba za a yi wa waɗanda suka kafirta izini ba, ba kuwa za a karɓi uzurin nasu ba.

85. Idan kuma waɗanda suka kafirta suka ga azaba, to ba za a sauƙaƙa musu ba, ba kuma za a saurara musu ba.

86. Idan kuma waɗanda suka yi tarayya (da Allah) suka ga ababen tarayyarsu (sai) su ce: “Ya Ubangijinmu, waɗannan su ne ababen tarayyarmu waɗanda muka zamanto muna bauta wa ba Kai ba.” Sai su jefa musu magana (cewa,): “Ku dai lalle maƙaryata ne!”

87. Kuma a wannan ranar suka miƙa wuya ga Allah; kuma duk abin da suka zamanto suna ƙirƙira ya ɓace musu.

88. Waɗanda suka kafirta suka kuma toshe hanyar Allah, to Mun ƙara musu azaba a kan azabar (da suka cancance ta) saboda ɓarnar da suka zamanto suna yi.

89. Kuma (ka tuna) ranar da za Mu tayar wa kowace al’umma da mai ba da shaida a kansu daga jinsinsu, Mu kuma zo da kai (Annabi Muhammadu) shaida a kan waɗannan (wato al’ummarka). Kuma Mun saukar maka da Littafi ne (wato Alƙur’ani) don bayani ga kowanne abu, kuma shiriya da rahama da bushara ga Musulmi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin da mushirikai za su tsinci kansu a ranar alƙiyama, ranar da zai tashi mai shaida daga kowace al’umma, watau manzon da ya aiko musu, domin ya ba da shaida a kan amsawar da suka yi masa, da waɗanda suka yi imani da waɗanda suka ƙi yin imani. Sannan daga lokacin ba za a ba wa kafirai wata damar gabatar da hanzarinsu game da kafircin da suka yi ba, ba kuma za a sake ba su damar komowa duniya ba don su gyara ɓarnarsu. Lahira kuwa ai gida ne na hisabi ba na aiki ba.
Haka kuma ya bayyana cewa, azzalumai za su ga azaba ƙarara, yayin da mala’iku za su zo suna janye da wutar Jahannama da linzami dubu saba’in, kowane linzami mala’ika dubu saba’in ne ke janye da shi. To a ranar ba za a taɓa sassauta musu azaba ba, ba kuma za a saurara musu ba; za su shige ta su kuma dawwama a cikinta har abada.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya labarta cewa, a wannan ranar idan mushirkai suka ga abubuwan da suka bauta wa ba Allah ba, sai su yi farat su faɗa wa Allah cewa, ai su ga waɗanda suka riƙa bauta wa a duniya maimakon su bauta masa. Sun faɗi haka ne kuwa domin su ɗora musu alhakin ɓatansu, wai su kuma a kuɓutar da su. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa waɗannan abubuwa da suka bauta wa ikon magana sai su mayar musu da martani cewa, lalle su mushirikai ƙarya suke da har suka mayar da su ababen bauta suka haɗa su da Allah suna bauta musu tare da shi, suka musanta cewa, su ba da umarninsu ko yardarsu suka yi shirkarsu ba. To a nan ne fa dole mushirikai suka saduda suka ƙara miƙa wuya ga Allah shi kaɗai, duk kuma ƙagen da suka dinga yi a duniya na cewa, gumakansu za su cece su a wurin Allah a lokacin ya ɓace musu ɓat.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana matakan azabar da wasu kafirai za su haɗu da su a lahira. Watau waɗanda suka kafirce suka kuma hana wasu bin tafarkin Allah, to Allah ya yi alƙawarin ƙara musu azaba ninkin-ba-ninkin saboda ɓarnar da suka tafka ta ɓata da ta ɓatarwa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tuna wa Annabi (ﷺ) ranar da zai tayar wa da kowace al’umma da manzonta domin ya ba da shaida a kan abin da suka aikata na imani ko na kafirci. Wannan manzon daga jinsinsu ne kuma yana magana ne da harshensu, don haka ya fi kowa sanin ayyukan al’ummarsa kuma zai fi kowa adalci da tausayi gare su. Ya bayyana wa Annabi cewa, shi ma a ranar zai zo da shi don gabatar da tasa shaidar ga al’ummarsa tare da sauran al'ummu gaba ɗaya. Ya kuma tabbatar masa da cewa, ya saukar masa da Alƙur’ani ne don bayanin duk wani abu da yake buƙatar bayaninsa wanda ya shafi haram da halal da sakamakon ayyuka na ƙwarai da waɗanda ba na ƙwarai ba. Ya kuma saukar da shi don ya zama shiriya ga mutane zuwa ga gaskiya, ya kuma zama rahama ga duk wanda ya riƙe shi ya yi aiki da shi, kuma albishir

ne ga muminai wanɗanda suka ba da gaskiya da Allah game da kyakkyawan sakamako na Aljanna da yake jiran su a lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Aya ta 90 ta ƙunshi umarni da adalci a cikin komai. Yin adalci ta fuskar sauke nauyin da ke kan bawa na dukiya ko na gangar jiki. Duk wani mai shugabanci babba ko ƙarami ya ba wa duk wanda yake ƙarƙashin shugabancinsa haƙƙinsa. Alƙali da wakilan shugabannin su ma su kula da haƙƙin da yake a wuyansu.
Hakanan adalcin da ke cikin mu'amalar saye da sayarwa da duk wata yarjejeniya ya ƙunshi zartar da duk abin da aka ƙulla yarjejeniyar a kansa ba tare da cuta ko ha'inci ba.
Adalci wajibi ne, kyautatawa kuma mustahabbi ce. Amfanar da mutane da dukiya da jiki da ilimi yana daga cikin ihsani; kai hatta kyautata wa dabbobi ma ihsani ne.

2. An ware kyautata wa dangi na kusa da ambato domin girman haƙƙinsu da ya rataya a wuyan mai hali ɗan'uwansu. Duk sanda wani ya fi kusanci da shi to haƙƙinsa a kansa ya fi girma.

3. Hana alfasha da munkari ya ƙunshi hana aikata duk wani zunubi da ya rataya da haƙƙin Allah ko na mutane. Hakanan hana zalunci ya ƙunshi hana duk wani nau'i na ta'addanci ga rayuka da dukiya ko mutuncin jama'a.
Don haka ayar ta ƙunshi duk wani umarni da hani da shari'a ta zo da shi.

Wata rana Alhasanul Basri ya karanta wannan ayar sai ya ce: "Lalle Allah ya tattara muku alheri gaba ɗayansa da sharri gaba ɗayansa a cikin aya guda. Na rantse da Allah babu abin da adalci da kyautatawa suka bari na ɗa'a ga Allah face sun tattaro shi, hakanan alfasha da munkari da zalunci ba su bar wani abu na saɓon Allah ba face sai da suka tattaro shi." [Al-Baihaƙi, Shu'abul Iman #138].

Suratun Nahl (90-93)
*إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُ بِٱلۡعَدۡلِ وَٱلۡإِحۡسَٰنِ وَإِيتَآيِٕ ذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَيَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِ وَٱلۡبَغۡيِۚ يَعِظُكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ ٩٠ وَأَوۡفُواْ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ إِذَا عَٰهَدتُّمۡ وَلَا تَنقُضُواْ ٱلۡأَيۡمَٰنَ بَعۡدَ تَوۡكِيدِهَا وَقَدۡ جَعَلۡتُمُ ٱللَّهَ عَلَيۡكُمۡ كَفِيلًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا تَفۡعَلُونَ ٩١ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّتِي نَقَضَتۡ غَزۡلَهَا مِنۢ بَعۡدِ قُوَّةٍ أَنكَٰثٗا تَتَّخِذُونَ أَيۡمَٰنَكُمۡ دَخَلَۢا بَيۡنَكُمۡ أَن تَكُونَ أُمَّةٌ هِيَ أَرۡبَىٰ مِنۡ أُمَّةٍۚ إِنَّمَا يَبۡلُوكُمُ ٱللَّهُ بِهِۦۚ وَلَيُبَيِّنَنَّ لَكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ مَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ ٩٢ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَكُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَلَٰكِن يُضِلُّ مَن يَشَآءُ وَيَهۡدِي مَن يَشَآءُۚ وَلَتُسۡـَٔلُنَّ عَمَّا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٩٣

90. Lalle Allah Yana umarni da yin adalci da kyautatawa da kuma bai wa makusanta (taimako), Yana kuma hana alfasha da mummunan aiki da zalunci. Yana gargaɗin ku don ku wa'azantu.

91. Ku kuma cika alƙawarin Allah idan kuka ɗauki alƙawari, kada kuma ku warware rantsuwa bayan kun ƙarfafa ta, alhali kuwa kun sanya Allah shaida a kanku. Lalle Allah Yana sane da abin da kuke aikatawa.

92. Kada kuma ku zamanto kamar (mace) wadda ta warware kaɗinta wara-wara bayan ƙarfinsa, kuna ɗaukar rantse-rantsenku yaudara a tsakaninku, don ganin kasancewar wata al'umma ta fi wata yawa da ƙarfi. Allah dai Yana jarabtar ku da shi (cika alƙawari) ne. Don kuma a ranar alƙiyama Ya bayyana muku abin da kuka kasance kuna saɓani a game da shi.

93. Da kuwa Allah Ya ga dama da Ya sanya ku al'umma ɗaya (masu addini ɗaya), sai dai kuma Yana ɓatar da wanda Ya ga dama Yana kuma shiryar da wanda Ya ga dama. Kuma tabbas za a tambaye ku game da abin da kuka kasance kuna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu dokokinsa ne waɗanda suke ƙunshe da umarni da hani, waɗanda kuma da su ne rayuwar ɗan'adam a bayan ƙasa za ta kyautata. Allah ya umarci bayinsa da tabbatar da adalci, watau bawa ya ba wa Allah haƙƙoƙinsa yadda ya kamata, hakanan ya ba wa 'yan'uwansa bayi haƙƙoƙinsu daidai ba tare da ya rage musu ba. Idan kuma zai yi hukunci ne a tsakaninsu to ya yi hukunci da adalci da gaskiya ba tare da nuna son zuciya ba. Sannan ya umarce su da kyautatawa, watau bawa ya bayar da abin da bai zama wajibi a kansa ba wajen ciyarwa ko yin afuwa ga wanda ya munana masa. Ya kuma umarce su da taimaka wa dangi makusanta ta hanyar ba su abin da suke buƙata na rayuwa. Ya kuma hana su aikata duk wani aiki mummuna, kamar zina ko wata mummunar magana. Hakanan ya hana su aikata duk wani abu da shari'a ta hana aikata shi na saɓon Allah. Ya hana su zalunci da nuna wa mutane girman kai da ta'addanci a kan rayukansu da dukiyoyinsu da mutuncinsu. Allah ya bayyana musu cewa, waɗannan bayanai da yake yi musu wa'azi ne yake musu domin su wa'azantu su riƙi abin da suka ji da muhimmanci su amfana a rayuwarsu ta duniya su tsira a lahira.
Sai kuma ya umarce su da su cika alƙawurran da suka yi tsakaninsu da Allah da waɗanda suka ɗauka tsakaninsu da junansu. Kuma kada su kuskura su warware rantsuwarsu bayan sun ƙarfafe ta da sunan Allah, sun kuma saka Allah tsakaninsu a matsayin shaida a kan alƙawarin da suka yi da juna cewa, za su cika shi; su tuna cewa, lalle Allah yana sane da duk abin da suke aikatawa, babu abin da yake ɓuya a gare shi, zai kuma yi wa kowa sakayya a kan aikinsa.
Ya sake jan kunnensu da kada su mayar da kansu wawaye marasa hankali ta hanyar warware alƙawarin da suka ɗauka. Watau kar su zama kamar wata sakaryar mata wadda take yini tana wahalar tufkar zare, sai maraice ya yi ta zauna ta yi ta warware abin da ta tufka, daga ƙarshe ta tashi fayau ba abin da ta tsinana wa kanta sai 'yar karen wahala da ta yini tana sha. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ja kunnensu da cewa, kada su mayar da rantse-rantsensu wata hanya ta yaudara kawai ba gaskiya a cikinta. Wasu su riƙa amfani da wannan rantsuwar ta ƙarya suna yaudarar wasu, don kawai su riƙa rantse wa mutanen da suka kula sun fi su yawa da ƙarfi domin su nutsu da su, amma idan sun sami damar cin amanarsu sai su ci.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, yana ba su wannan umarni ne na cika alƙawari kowane iri ne don ya jarrabe su ya ga ko za su riƙa cikawar ko ba za su cika ba? Kuma don ya bayyana musu abin da suke saɓani a kansa a duniya ta nuna mai gaskiya da marar gaskiya, mai cika alƙawari da mayaudari.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Tabbas duk wani mayaudari (mai warware alƙawari) za a kafa masa tutarsa kusa da shi ranar alƙiyama sai a yi shela cewa,: 'Wannan ita ce yaudarar da wane ɗan wane ya yi.' [Bukhari#6177, 6178 da Muslim#1735]

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da ya ga dama da ya mayar da su al'umma ɗaya a kan addini guda na gaskiya babu wani saɓani a tsakaninsu. To amma ba haka hikimarsa ta gudana ba; ya zamanto yana ɓatar da wanda ya ga dama domin shi ya zaɓi ɓatan, ya kuma shiryar da wanda ya ga dama domin shi ya so shiriyar; ya datar da wanda ya ga dama da falalarsa, ya zamanto mai cika alƙawurran da ya ɗauka. Hakanan kuma lalle a ranar alƙiyama tabbas sai ya yi musu tambayoyi ɗaya bayan ɗaya game da abin da suka aikata a nan duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cika alƙawarin da mutum ya ɗauka shi yake taimaka masa wajen samun tabbatar dugadugansa a kan tafarki madaidaici. Rashin haka kuwa shi yake kawo zamewa daga kan turba ta ƙwarai.

2. Guje wa karɓar rashawa da cin hanci domin warware alƙawari da ha’inci.

3. Kwaɗaitarwa a kan guje wa abin duniya, musamman wanda zai cutar da mumini a addininsa da mutuncinsa, ko ya shagaltar da shi daga ayyukan da suka wajaba a kansa.

4. Masu ilimi da hankali su ne waɗanda ba su yarda su fifita abu mai gushewa a kan mai wanzuwa ba har abada, komai yawansa kuwa.

5. Girman ladan haƙuri a bisa bin Allah da guje wa saɓa masa, da haƙuri a kan abin da ya faru na ƙaddara. Allah yana ninninka ladan masu haƙuri ninki mai yawa.

6. Imani sharaɗi ne na ingancin duk wani aiki na ƙwarai da karɓuwarsa a wurin Allah. Komai kyan aiki idan mai yinsa ba shi da imani to aikinsa ba karɓaɓɓe ne a wurin Allah ba.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa mumini mai kyakkyawan aiki alƙawarin ba shi kyakkyawar rayuwa a nan duniya wadda ta haɗa da samun natsuwar zuciya da dangana da abin da Allah ya ba shi da samun dacewa, a kan ayyukan ɗa’a ga Allah. Sannan a lahira ya yi masa sakamakon da ya fi ƙarfin ayyukansa masu kyau.

Suratun Nahl (94-97)

وَلَا تَتَّخِذُوٓاْ أَيۡمَٰنَكُمۡ دَخَلَۢا بَيۡنَكُمۡ فَتَزِلَّ قَدَمُۢ بَعۡدَ ثُبُوتِهَا وَتَذُوقُواْ ٱلسُّوٓءَ بِمَا صَدَدتُّمۡ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَكُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ٩٤ وَلَا تَشۡتَرُواْ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ ثَمَنٗا قَلِيلًاۚ إِنَّمَا عِندَ ٱللَّهِ هُوَ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٩٥ مَا عِندَكُمۡ يَنفَدُۖ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ بَاقٖۗ وَلَنَجۡزِيَنَّ ٱلَّذِينَ صَبَرُوٓاْ أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩٦ مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَنُحۡيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةٗ طَيِّبَةٗۖ وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩٧

94. Kuma kada ku ɗauki rantse-rantsenku yaudara a tsakaninku, sai ƙafafuwanku su zame bayan tabbatarsu, kuma ku ɗanɗani azaba saboda toshe hanyar Allah da kuka yi; kuma (a lahira) kuna da azaba mai girma.

95. Kada kuma ku sayar da alƙawarin Allah da ɗan kuɗi ƙanƙani. Lalle abin da yake wurin Allah shi ya fi muku alheri in kun kasance kun san (haka).

96. Abin da yake wurinku yana ƙarewa; abin da kuwa yake wurin Allah wanzajje ne. Lalle kuwa tabbas za Mu saka wa waɗanda suka yi haƙuri ladansu da mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa.

97. Wanda ya yi kyakkyawan aiki namiji ko mace alhali shi yana mumini, to lalle za Mu raya shi rayuwa mai daɗi, kuma za Mu saka musu ladansu da mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da gargaɗi a kan cin amana da warware rantsuwa da mummunan sakamakon mai aikata hakan. Allah ya hani mutane da mayar da rantse-rantsensu wata hanyar yaudarar juna da bin son zuciya, su riƙa rantsuwa suna kuma warware ta duk sanda suka ga dama. Ya bayyana musu cewa, idan sun ci gaba da aikata haka to dugadugansu za su zame daga kan tafarki madaidaici bayan a da suna tsaye a kansu kyam, sannan kuma a lahira za su ɗanɗani azaba sakamakon ɓacewarsu daga kan hanya da ɓatar da wasu da suka yi. Domin Allah zai ninninka musu azaba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana su karɓar ɗan kuɗi kaɗan na rashawa da cin hanci don su warware alƙawarin da aka yi da su su ƙi cikawa. Ya tabbatar musu cewa, abin da yake wurin Allah na sakamako na nan duniya da na lahira ga wanda ya nemi yardar Allah, ya fi alheri a kan abin da za a ba su na tarkacen duniya mai ƙarewa in sun zamanto sun san da haka. Ya tabbatar musu da cewa, duk abin da mutane suke tarawa na dukiyoyi da jin daɗin duniya komai yawansu mai ƙarewa ne wata rana, amma abin da yake wajen Allah na sakamako wanzajje ne. To mene ne ya sa suke fifita abin da yake gushewa a kan abu mai wanzuwa?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, lalle zai saka wa masu haƙurin kiyaye alƙawuransu da rantsuwarsu da kyakkawan sakamako sabado abin da suka zamanto suna aikatawa na ɗa'a gare shi, domin kuwa a kan duk wani aikin kirki ɗaya zai ninka musu shi har goma zuwa ninki ɗari bakwai, har zuwa ninki barkatai ba iyaka.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawari ga duk mutumin da ya yi imani ya yi aiki na ƙwarai, namiji ne shi ko mace, to zai ba shi kyakkyawar rayuwa a nan duniya, a lahira kuwa zai saka masa da mafi kyan abin da ya kasance yana aikatawa na kyawawan ayyuka.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya musulunta kuma aka ba shi abin da zai ishe shi rayuwa, Allah ya sa masa dangana da abin da ya ba shi, to lalle wannan ya sami babban rabo." [Muslim #1054].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah ba ya zaluntar mumini daidai da kyakkyawan aiki ɗaya; a sanadiyyarsa Allah zai ba shi a nan duniya, ya kuma saka masa a lahira a kansa. To amma kafiri za a ciyar da shi da kyawawan ayyukansa a nan duniya, idan kuma ya je lahira to ba shi da wani aikin ƙwarai da za a saka masa da alheri a kansa." [Muslim #2808].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Malamai sun haɗu a kan cewa, buɗe karatun Alƙur'ani da neman tsari daga Shaiɗan mustahabbi ne ba wajibi ba.

2. Hikimar neman tsarin Allah daga Shaiɗan da mai karatu zai yi ita ce, domin kada Shaiɗan ya rikirkita masa karatunsa yana hana shi tuntuntuni a kan ayoyin da yake karantawa.

3. Muminai masu yawan ambaton Allah da mayar da al'amuransu gare shi, Shaiɗan ba zai iya cin galaba a kansu ba, balle ma ya hallakar da su.

4. Yawan gafala daga ambaton Allah ita ce ƙofar samun galabar Shaiɗan a kan ɗan'adam.

Suratun Nahl (98-100)
فَإِذَا قَرَأۡتَ ٱلۡقُرۡءَانَ فَٱسۡتَعِذۡ بِٱللَّهِ مِنَ ٱلشَّيۡطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ ٩٨ إِنَّهُۥ لَيۡسَ لَهُۥ سُلۡطَٰنٌ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ يَتَوَكَّلُونَ ٩٩ إِنَّمَا سُلۡطَٰنُهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ يَتَوَلَّوۡنَهُۥ وَٱلَّذِينَ هُم بِهِۦ مُشۡرِكُونَ ١٠٠

98. To idan za ka karanta Alƙur'ani sai ka nemi tsarin Allah daga Shaiɗan korarre (daga rahamar Allah).

99. Lalle shi (Shaiɗan) ba shi da iko a kan waɗanda suka yi imani kuma suke dogara da Ubangijinsu.

100. Ikonsa kawai yana kan waɗanda suke jiɓintar sa da kuma waɗanda suke yin tarayya da shi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, idan mutum zai fara karatun Alƙur'ani to ya buɗe shi da neman tsarin Allah daga waswasin Shaiɗan wanda Allah ya kore shi daga rahamarsa. Ya bayyana cewa, Shaiɗan ba shi da wani iko a kan waɗanda suka yi imani da Allah, suke kuma dogara da shi a cikin dukkan al'amuransu na yau da kullum. Inda kawai Shaiɗan yake samun ikonsa shi ne a kan mutanen da suka jiɓince shi suka riƙa yi masa biyayya a kan abin da yake ruɗar su da shi, waɗanda har ta kai suna yin shirka da Allah saboda bin ruɗin Shaiɗan gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shafe wasu hukunce-hukuncen Alƙur'ani lokacin da yake sauka tabbataccen abu ne, saboda wata hikima ta Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wadda ta danganci wata maslaha, ko faruwar wasu sababbin al'amura, ko canjin yanayin zamantakewa ta mutane.

2. Sukan da masu ƙaryata Alƙur'ani suke yi don samuwar shafe wasu hukunce-hukunce a cikinsa suka ne marar tushe, domin masu yin sa ba su san komai ba dangane da hikimomin shari'a.

3. Daga cikin manyan manufofin saukar da Alƙur'ani akwai tabbatar da dugadugan muminai a kan gaskiya da ƙarfafa musu imani, saboda ya ƙunshi ƙarfafan dalilai da hujjoji bayyanannu masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah da nuna cikakkiyar Kudurarsa da yalwar iliminsa.

4. Zargin Annabi (ﷺ) da cewa, ya koyi Alƙur'ani daga wani bawa ba'ajame zargin banza ne da ko ƙaramin mai hankali zai fahimci ɓacinsa, domin harshen da wannan bawan yake magana da shi ajamanci ne ba Larabci ba, Annabi (ﷺ) kuma ba ya fahimtar wannan harshen kamar yadda su ma ba sa fahimtar sa, shi kuma Alƙur'ani da Annabi (ﷺ) yake karanta musu da tantagaryar Larabci yake wanda duk suna fahimtar sa, to ta yaya za a ce ya koyo shi daga mutumin da bai iya magana da Larabci ba? Bugu da ƙari, kuma su mutane ne masu fasahar gaske da iya sarrafa harshensu na Larabci da kowa ya san su da haka, to amma ga shi sun kasa kawo kamar Alƙur'ani su da sauran Larabawa gaba ɗaya, to sai kuma ga shi suna jingina shi ga wani bagwari wanda ba Balarabe ba?

5. Maƙaryaci yana ƙirƙirar ƙarya ne ba tare da ya yi tunanin yadda ƙaryar tasa take tafiya a baibai ba, sai ya zamanto fahimtar maganarsa kaɗai ta isa ta sa a gane ɓarna da tufka da warwarar da ke cikinta.

Suratun Nahl (101-105)

وَإِذَا بَدَّلْنَآ ءَايَةً مَّكَانَ ءَايَةٍ وَٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا يُنَزِّلُ قَالُوٓاْ إِنَّمَآ أَنتَ مُفْتَرِۭ ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٠١﴾ قُلْ نَزَّلَهُۥ رُوحُ ٱلْقُدُسِ مِن رَّبِّكَ بِٱلْحَقِّ لِيُثَبِّتَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهُدًى وَبُشْرَىٰ لِلْمُسْلِمِينَ ﴿١٠٢﴾ وَلَقَدْ نَعْلَمُ أَنَّهُمْ يَقُولُونَ إِنَّمَا يُعَلِّمُهُۥ بَشَرٌ ۗ لِّسَانُ ٱلَّذِى يُلْحِدُونَ إِلَيْهِ أَعْجَمِىٌّ وَهَٰذَا لِسَانٌ عَرَبِىٌّ مُّبِينٌ ﴿١٠٣﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ لَا يَهْدِيهِمُ ٱللَّهُ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿١٠٤﴾ إِنَّمَا يَفْتَرِى ٱلْكَذِبَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ ۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْكَٰذِبُونَ ﴿١٠٥﴾

101. Idan kuma Muka musanya wata aya a madadin wata ayar, alhali kuwa Allah ne Mafi sanin abin da Yake saukarwa, sai su ce: "Kai dai mai ƙirƙirar ƙarya ne kawai!" A'a, ba haka ba ne, yawancinsu ba su san (komai) ba ne.

102. Ka ce: "*Ruhul Kudusi* (wato Mala'ika Jibrilu) ne ya saukar da shi daga Ubangijinka da gaskiya don ya tabbatar da waɗanda suka yi imani (a kan dugadugansu), kuma shiriya ne da albishir ga Musulmai."

103. Kuma haƙiƙa Mun san lalle suna cewa,: “Wani mutun ne kawai yake koya masa shi.” Harshen wanda suke karkata zuwa gare shi ajami ne, wannan kuwa harshe ne na Larabci bayyananne.

104. Lalle waɗanda ba sa yin imani da ayoyin Allah, to Allah ba zai shirye su ba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi.

105. Waɗanda ba sa yin imani da ayoyin Allah su ne kawai suke ƙirƙirar ƙarya; kuma waɗannan su ne maƙaryata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakarcin mushirikai da raunin hankalinsu da ƙarancin fahimtarsu, saboda yadda suka nuna wa Manzon Allah (ﷺ) rashin gaskiyarsu a fili, inda ya ce, duk sanda ya shafe wani hukunci na shari’a ya kawo wani sabo a madadinsa, duba da maslaha da buƙata wadda shi ya fi kowa sanin ta game da hukunce-hukuncen da yake saukarwa ga bayinsa, sai kafirai su riƙa cewa, Annabi (ﷺ) ne yake ƙirƙirar ayoyi yana kuma sake canja su duk sanda ya ga dama, watau ba su yarda aikin Allah ne ba. Allah ya mayar musu da martani cewa, yawancinsu ba su san hikimomin da ke ƙunshe cikin canja wasu hukunce-hukunce da waɗansu ba.
Ya kuma umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, Mala’ika Jibrilu shi ne ya sauko da Alƙur’ani da gaskiya daga Ubangiji, babu wani kuskure ko jirkitarwa a cikinsa, kuma ba ƙirƙirarsa ba ce. Ya kuma bayyana musu wasu manufofin saukar da Alƙur’ani da canja wasu hukunce-hukuncensa, shi ne domin ya tabbatar da dugadugan waɗanda suka yi imani da shi, su daɗa samun yaƙini duk lokacin da wani hukunci sabo ya sauko ko aka shafe wani hukunci da wani; don haka su tarbiyyantu da ilimominsa su ɗabi’antu da kyawawan halaye da yake koyarwa. Sannan kuma ya zamanto musu shiriya da gaskiya kuma albishir da lada mai yawa ga Musulmi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin irin ƙaryar da mushirikai suka riƙa yi a kan Annabi (ﷺ). Bayan waccan tuhumar da suka yi masa ta cewa, yana yi wa Allah ƙarya, sai kuma suka sake zuwa da wata tuhumar daban wadda take nuna rashin sanin alƙibla da kame-kamen da suke ciki. Sun zargi Annabi (ﷺ) da cewa wai yana koyo Alƙur’ani ne daga wurin wani bawa matashi ba’ajame, watau wanda ba Balarabe ba. Wannan matashi bawa ne na wasu Kuraishawa a garin Makka. Ya kasance yana kasuwancinsa na saye da sayarwa a kusa da dutsen Safa, bai ma iya magana da Larabci ba sai ɗan abin da ba a rasa ba na ya amsa tambaya idan an tambaye shi. To Annabi (ﷺ) ya kasance yana zama wurinsa yana taɗi da shi a wani lokaci, sai mushirikai suka riƙa zargin cewa, wai shi ne yake koya wa Manzon Allah (ﷺ) karatun Alƙur’ani da suke ji daga bakinsa. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani mai sauƙin fahimta, mai kuma nuna sakarcin waɗannan mutane. Allah ya bayyana cewa, shi wannan bawan fa harshensa da yake magana da shi ajamanci ne ba Larabci ba, shi kuma Alƙur’ani ya sauka ne da harshen Larabci mai cike da fasaha bayyananna, wanda kuka ya gagari kowa, to ta yaya wanda bai iya Larabci ba zai iya koyar da wannan Alƙur’ani?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai su ne manyan maƙaryata, domin su ne ba su yi imani da ayoyin Allah ba, don haka ya ƙi yi musu katarin dacewa da shiriya, kuma za su ci gaba da zama a haka matuƙar sun ci gaba da abin da suke aikatawa, kuma suna da azaba mai raɗaɗi a dalilin kafircinsu da ƙaryata ayoyin Allah.
Ya sake tabbatar musu da cewa, Annabi (ﷺ) ba maƙaryaci ne ba dangane da abin da ya zo musu da shi daga Allah. Asharari su ne maƙaryata waɗanda ba su yi imani da ayoyin Allah ba, domin ba sa tsoron azabarsa, ba sa kuma tunanin samun wani lada daga wajensa; to waɗannan su ne tatattun maƙaryata. Amma Manzon Allah (ﷺ) an san shi kyakkyawan sani; ya fi kowa gaskiya a cikin mutanensa kakaf, babu wani mai kokwanto game da haka, har ta kai suna yi masa laƙabi da ‘Al-Amin’, watau mai amana. Don haka lokacin da Hiraƙlu Sarkin Rumawa ya yi wa Abu Sufyan wasu tambayoyi da suka shafi Annabi (ﷺ), daga cikinsu yana cewa,: Shin kun kasance kuna tuhumar sa da ƙarya ne kafin ya fara faɗar maganganun da

yanzu yake faɗa? Abu Sufyan ya amsa masa da cewa: A'a. Sai Hiraklu ya ce: "Ba za ta taba yiwuwa ba bai yi wa mutane ƙarya ba sannan ya zo yana yi wa Allah ƙarya." [Bukhari #7].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin aikata kafirci na magana ko na aiki yayin da aka tilasta wa mutum aikatawa. Tilastawa ita ce hana wa mutum 'yancin zaɓin kansa saboda barazanar kashe shi ko salwantar masa da wata gaba ta jikinsa ko yi masa azabar da zai kasa jurewa daga wanda zai zartar da abin da ya yi barazanar aikata masa.

2. Duk da wannan sauki da aka samu, wasu malamai sun ambato haɗuwar malamai a kan cewa, wanda ya zabi a kashe shi a kan furta ko aikata kafirci, ya yi hakuri ya jure, to ya fi falala a kan wanda ya zabi sauki.

3. Dauriyar da hakurin sukan wajaba a kan wasu masu girman matsayi a cikin al'umma waɗanda bayyana kafircinsu a sarari zai jawo canja addinin Allah cikin al'umma. Wannan shi ne matakin da annabawa suke kai, ba za su furta wani abu na kafirci ba saboda tursasawar wani sai dai a kashe su. Hakanan wasu ma daga cikin manyan wannan al'umma sun fifita hakan saboda girman matsayinsu.

4. Wajibi ne ga wanda aka matsa masa sai ya furta ko aikata kafirci ya ki abin a zuciyarsa, idan ba haka ba kuwa to ya nuna ya zabi kafirci ne ya yarda da shi.

5. To idan an karɓi hanzarin wanda aka tilasta masa yin kafirci ba da yardarsa ba, wannan ya nuna dacewar karɓar hanzarin wanda aka tilasta masa sakin matarsa ko 'yanta bawansa ko sayar da kayansa ko sayen na wani da makamantan haka ba da amincewarsa ba. Duk waɗannan abubuwa ba za su tabbata ba idan an yi su ta hanyar tilastawa da aka ambata a baya.

6. Shagalta da tara abin duniya da neman jin daɗinta da fifita waɗannan a kan sha'anin lahira abu ne da yake haifar da kauce wa hanyar Allah.

Suratun Nahl (106-109)

مَن كَفَرَ بِٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ إِيمَٰنِهِۦٓ إِلَّا مَنۡ أُكۡرِهَ وَقَلۡبُهُۥ مُطۡمَئِنُّۢ بِٱلۡإِيمَٰنِ وَلَٰكِن مَّن شَرَحَ بِٱلۡكُفۡرِ صَدۡرٗا فَعَلَيۡهِمۡ غَضَبٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَلَهُمۡ
عَذَابٌ عَظِيمٞ ١٠٦ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمُ ٱسۡتَحَبُّواْ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا عَلَى ٱلۡأٓخِرَةِ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ١٠٧ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ طَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ
وَسَمۡعِهِمۡ وَأَبۡصَٰرِهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡغَٰفِلُونَ ١٠٨ لَا جَرَمَ أَنَّهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ١٠٩

106. Wanda ya kafirce wa Allah bayan imaninsa, sai dai wanda aka tilasta wa alhali kuwa zuciyarsa ta cika da imani, amma kuma wanda ya buɗe wa kafirci ƙirjinsa, to (waɗannan) fushin Allah ya tabbata a kansu kuma suna da azaba mai girma.

107. Wannan kuwa (ya faru) saboda su sun fi son rayuwar duniya a kan ta lahira, kuma lalle Allah ba Ya shiryar da mutane kafirai.

108. Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya doɗe zukatansu da jinsu da ganinsu, kuma waɗannan su ne gafalallu.

109. Ba shakka lalle su a lahira su ne taɓaɓɓu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin wasu kaso biyu na mutane a Makka dangane da imaninsu da Musuluncinsu:
Kaso na farko, su ne waɗanda aka tilasta musu furta kalmar kafirci ko aikata shi bayan imaninsu, amma zukatansu a natse suke da imani da ƙin kafirci. Kamar yadda ya faru ga Ammar ɗan Yasir (Allah ya ƙara masa yarda) lokacin da mushirikai suka riƙa yi masa azaba a kan sai ya kafirce wa Annabi (ﷺ), har wahala ta kai shi ga furta kalmar da suka nemi ya furta ta kafirci. Daga bisani ya zo ya shaida wa Annabi (ﷺ) abin da ya faru, Manzon Allah ya karɓi hanzarinsa.
Kaso na biyu, su ne waɗanda suka kafirta bayan imaninsu tare da jin gamsuwa da kafircin a zuciyarsu, to waɗannan su ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci azaba nau'i shida da ya tanadar musu:
(a) Fushin Allah mai tsanani.
(b) Azaba mai girma da take jiran su, saboda sun fifita rayuwar duniya a kan ta lahira, sun amince da yarda da mushirikai ko da kuwa za su fusata Ubangijinsu.
(c) Allah ba zai shiryar da su ba, don haka sun rasa gamon katari daga Allah.
(d) Allah ya doƙe zukatansu, ba za su taɓa fahimtar wa'azi ba, ya doƙe jinsu ba za su taɓa sauraron abin da zai yi musu amfani ba, hakanan ya doƙe ganinsu ba za su taɓa ganin dalilan da za su sa su yi imani ba.
(e) Sun tabbata su ne gafalallu da suka rasa fahimtar hanyoyin da za su kai su ga arziki na har abada ko taɓewa ta har abada.
(f) Ya tabbata su ne hasararru waɗanda suka yi hasarar kawunansu a duniya da lahira, suka rasa gidan Aljanna yayin da suka saki imaninsu suka riƙi kafirci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar sahabban da suka yi hijira suka yi jihadi tare da Manzon Allah (ﷺ).

2. Jajircewa a kan addini da aiki da koyarwarsa ita ce hanyar da mutum zai sami babban tagomashi daga Allah, ya samu gafarar zunubbansa manya da ƙanana, ya kuma sami kariya ta Allah tare da dacewa da babbar rahama tasa.

3. Ranar lahira rana ce da kowa ta kansa yake, don haka abin da ya wajaba ga bawa shi ne kyautata ayyukansa tun daga nan duniya, kada ya dogara a kan samun ceton wasu ba tare da kyautata aiki ba.

Suratun Nahl (110-111)

ثُمَّ إِنَّ رَبَّكَ لِلَّذِينَ هَاجَرُواْ مِنۢ بَعۡدِ مَا فُتِنُواْ ثُمَّ جَٰهَدُواْ وَصَبَرُوٓاْ إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعۡدِهَا لَغَفُورٞ رَّحِيمٞ ١١٠ يَوۡمَ تَأۡتِي كُلُّ نَفۡسٖ تُجَٰدِلُ عَن نَّفۡسِهَا وَتُوَفَّىٰ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا عَمِلَتۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ١١١

110. Sannan lalle Ubangjinka (Mai gafara ne da jin ƙai) ga waɗanda suka yi hijira bayan an fitine su, sannan suka yi jihadi suka kuma yi haƙuri, lalle Ubangijinka, bayansu (waɗannan ayyuka) Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

111. Ranar da kowanne rai zai zo yana kare kansa, kuma a cika wa kowanne rai (sakamakon) abin da ya aikata, kuma su ba za a zalunce su ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kason mutane masu rauni a Makka waɗanda mushirikai suka fitine su da kafirci, suka matsa musu har suka furta shi ko suka aikata shi, daga bisani suka samu kuɓuta suka yi hijira zuwa Madina, suka bar danginsu da dukiyoyinsu don neman yardar Allah da gafararsa kaɗai. Suka gauraya da sauran 'yan'uwansu Musulmi suka yaƙi kafirai tare da su, suka kuma jure

wajen bin Allah da Manzonsa da guje wa saɓa wa Allah da haƙuri a kan duk wani abin ƙi da zai same su. To Allah ya tabbatar musu da cewa, ya gafarta musu wancan abin da ya faru a baya na bayyana kafirci da suka yi kuma shi mai jin ƙai ne a ranar lahira, ranar da kowane mutum ta kansa yake, ba ya ta iyayensa ko ‘ya’ya ko mata ko wani ɗan’uwa, a ranar kowane rai za a cika masa sakamon ayyukan da ya yi a duniya kyawawa da munana, babu wanda za a rage masa komai a aikinsa mai kyau ko a ƙara masa wani wanda bai yi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu abin da yake tsare wa kowace al’umma ni’imomin da Allah ya yi mata sai imani da Allah da ayyuka na ƙwarai.

2. Allah yana sakayya ne gwargwadon jinsin ayyuka. Yayin da mutanen Makka suka butulce wa ni’imar Allah suka juya masa baya, sai ya jarrabe su da kishiyoyin ni’imomin da ya yi musu da farko. Ya jarrabe su da yunwa maimakon yalwar arziki, ya jarrabe su da tsoro mai tsanani a madadin aminci da kwanciyar hankali.

3. An gabatar da ambaton aminci, watau zaman lafiya, kafin ambaton nutsuwa domin nutsuwa ba za ta samu ba sai da zaman lafiya. Wannan yana nuna muhimmancin zaman lafiya a rayuwar ɗan’adam.

Suratun Nahl (112-113)
وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا قَرۡيَةٗ كَانَتۡ ءَامِنَةٗ مُّطۡمَئِنَّةٗ يَأۡتِيهَا رِزۡقُهَا رَغَدٗا مِّن كُلِّ مَكَانٖ فَكَفَرَتۡ بِأَنۡعُمِ ٱللَّهِ فَأَذَٰقَهَا ٱللَّهُ لِبَاسَ ٱلۡجُوعِ وَٱلۡخَوۡفِ بِمَا كَانُواْ يَصۡنَعُونَ ١١٢ وَلَقَدۡ جَآءَهُمۡ رَسُولٞ مِّنۡهُمۡ فَكَذَّبُوهُ فَأَخَذَهُمُ ٱلۡعَذَابُ وَهُمۡ ظَٰلِمُونَ ١١٣

112. Allah kuma Ya ba da misali da wata alƙarya wadda ta kasance cikin aminci da kwanciyar hankali, arzikinta yana zo mata a yalwace ta kowanne wuri, sai ta kafirce wa ni’imomin Allah, to sai Allah Ya ɗanɗana mata masifar yunwa da tsoro saboda abin da suka kasance suna aikatawa.

113. Haƙiƙa kuma Manzo ya zo musu daga cikinsu, sai suka ƙaryata shi, to sai azaba ta afka musu alhali suna azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da misali da garin Makka wanda ya kasance cikin aminci da kwanciyar hankali, ga arzikinsu yana zuwa musu ta ko’ina a yalwace, a lokacin da sauran garuruwa maƙota suka rasa duk waɗannan abubuwa. To amma maimakon mutanen Makka su gode wa Allah game da waɗannan ni’imomi da ya yi musu su yi imani da Manzon da Allah ya aiko musu, sai suka kafirce wa ni’imomin Allah, suka ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) wanda shi ne mafi girman ni’imar da Allah ya ba su. A sakamakon haka Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jarrabe su da wata matsananciyar yunwa, fari ya mamaye su har sai da ta kai mutane suna cin kashin raƙuma haɗe da jininsu. Ya kuma jarrabe su da matsanancin tsoro; domin bayan sun kori Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa sun yi hijira zuwa Madina, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafi Manzonsa da muminai suka zama runduna mai ƙarfin gaske; wannan ya jefa kafiran Kuraishawa cikin tsoro da fargabar kada Annabi (ﷺ) ya kawo musu hari har gida. Daga ƙarshe Allah ya ba shi nasara ya cinye garin Makka da yaƙi.
Allah ya bayyana cewa, ya yi musu wannan jarrabar ce saboda abin da suka riƙa aikatawa na kafirci da butulci ga ni’imar Allah.
Sai kuma ya ƙara bayyana halin Kuraishawa wanda ya jawo musu musibar da ta same su, ya tabbatar da cewa, ya aiko musu da Manzo, watau Annabi Muhammadu (ﷺ), wanda sun san amanarsa da gaskiyarsa sarai, amma sai suka ƙaryata shi, suka ƙaryata Alƙur’ani da Allah ya saukar masa, don haka azaba ta auka

musu ta yunwa da tsoro, kuma su ne suka zalunci kansu, domin su ne suka kai kawunansu wuraren halaka yayin da suka zabi su yi wa Allah shirka, su ƙaryata Manzonsa (ﷺ).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin wajabcin cin arziki na halal da gode wa ni'imar Allah.

2. Halattawa da haramtawa haƙƙin Allah ne shi kaɗai. Ba ya halatta ga wani ya riƙa yanke hukuncin halal da haram ba tare da wata hujja daga Allah da Manzonsa ba. Wanda duk ya yi haka to ya ƙaga wa Allah ƙarya, ba zai taba rabauta ba duniya da lahira sai idan ya tuba zuwa ga Allah.

3. Allah bai haramta mana wani abu ba sai wanda yake mummuna mai cutarwa ko ƙazanta.

4. Yawaita sabon Allah yana jawo wa bawa shiga matsatsi da wahalar da kai a rayuwa.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cikakken adali ne ba ya yi wa mutum uƙuba sai ya cancanci ya yi masa ita.

6. Rahamar Allah ta gudana a kan karɓar tuban bayinsa waɗanda suka aikata munanan ayyuka na kafirci da sabon Allah sannan suka tuba suka kyautata aikinsu, to waɗannan Allah zai karɓi tubansu.

Suratun Nahl (114-119)

فَكُلُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ حَلَٰلًا طَيِّبًا وَٱشۡكُرُواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ إِن كُنتُمۡ إِيَّاهُ تَعۡبُدُونَ ١١٤ إِنَّمَا حَرَّمَ عَلَيۡكُمُ ٱلۡمَيۡتَةَ وَٱلدَّمَ وَلَحۡمَ ٱلۡخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ لِغَيۡرِ ٱللَّهِ بِهِۦۖ فَمَنِ ٱضۡطُرَّ غَيۡرَ بَاغٖ وَلَا عَادٖ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١١٥ وَلَا تَقُولُواْ لِمَا تَصِفُ أَلۡسِنَتُكُمُ ٱلۡكَذِبَ هَٰذَا حَلَٰلٞ وَهَٰذَا حَرَامٞ لِّتَفۡتَرُواْ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَفۡتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ لَا يُفۡلِحُونَ ١١٦ مَتَٰعٞ قَلِيلٞ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١١٧ وَعَلَى ٱلَّذِينَ هَادُواْ حَرَّمۡنَا مَا قَصَصۡنَا عَلَيۡكَ مِن قَبۡلُۖ وَمَا ظَلَمۡنَٰهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ١١٨ ثُمَّ إِنَّ رَبَّكَ لِلَّذِينَ عَمِلُواْ ٱلسُّوٓءَ بِجَهَٰلَةٖ ثُمَّ تَابُواْ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ وَأَصۡلَحُوٓاْ إِنَّ رَبَّكَ مِنۢ بَعۡدِهَا لَغَفُورٞ رَّحِيمٞ ١١٩

114. To ku ci halal mai daɗi daga abin da Allah Ya arzuta ku da shi, kuma ku gode ni'imomin Allah in kun kasance Shi kaɗai kuke bauta wa.

115. Abin da kawai Ya haramta muku (shi ne) mushe da jini (mai kwarara) da naman alade da kuma abin da aka yanka da (sunan) wanin Allah; amma wanda ya matsu (ya ci) ba yana mai zalunci ko ƙetare iyaka ba, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

116. Kuma saboda abin da harsunanku suke bayyanawa na ƙarya kada ku riƙa cewa, wannan halal ne, wannan kuma haram ne, don ku yi wa Allah ƙarya. Lalle waɗanda suke ƙirƙira wa Allah ƙarya ba sa rabauta.

117. (Wannan) jin daɗi ne ƙanƙani (a duniya), kuma suna da azaba mai raɗaɗi.

118. Kuma Mun haramta wa Yahudawa abin da Muka labarta maka tun tuni; ba Mu kuwa zalunce su ba, sai dai kuma kansu suka zalunta.

119. Sannan lalle Ubangijinka (Mai gafara ne) ga waɗanda suka aikata mummuna a cikin jahilci sannan suka tuba bayan haka suka kuma gyara, lalle Ubagijinka Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa da cin abubuwan da suke na halal masu daɗi waɗanda Allah ya arzuta su da su, ya kuma umarce su da gode wa ni'imomin da ya yi musu ta hanyar jingina masa su da sarrafa su a inda ya yarda a saka su, domin shi ne kaɗai wanda ya cancanci a bauta masa; idan haka ne kuwa to dole su bi wannan umarni nasa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu abin da ya haramta musu wanda amfani da shi zai cutar da su a rayuwarsu ta duniya da ta lahira da cewa, ya haramta musu cin naman mushe da jinin da ya kwarara lokacin da aka yanka dabba, da naman alade da duk wata dabba da aka yanka ta ba da sunan Allah ba, ko aka yanka ta don neman kusanci ga wanin Allah. To amma wannan hukunci ya danganci lokacin da mutum yake da zaɓi ne, amma idan ya sami kansa a cikin halin larura ya kuma rasa abin da zai ci ya rayu sai ɗaya daga cikin waɗannan abubuwan, don haka ya ci ba don yana kwaɗayin cin haram ba, to wannan ko ya ci ba shi da laifi. Lalle Allah zai gafarta masa wannan, kuma shi Allah mai tausayi ne gare shi don haka ne ma ya halatta masa cin abin da ya haramta masa saboda halin larura.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar a kan bin tafarki na mushirikai waɗanda suka riƙa haramta cin naman wasu dabbobi ko hawan su ko ɗora musu kaya da ƙaryar cewa, na gumakansu ne ba tare da wata hujja daga Allah ba. Allah ya tsawatar musu da cewa, kada su ci gaba da ƙirƙirar ƙarya da harsunansu suna jingina ta ga Allah, su ce abu kaza halal ne abu kaza haramun ne, don kawai su ƙaga wa Allah ƙaryar cewa, ya haramta abin da bai haramta ba, ko ya halatta abin da bai halatta ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, duk wanda yake ƙirƙira wa Allah ƙarya ba zai taɓa rabauta ba duniya da lahira. A duniya zai ji ɗan daɗi ne kaɗai ba mai ɗorewa ba, a lahira kuwa zai haɗu da azaba ce mai raɗaɗi wadda ba za ta yanke ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya labarta mana horon da ya yi wa Yahudawa, ya tsananta musu hukuncin wasu abubuwa masu daɗi ya haramta musu amfani da su, saboda yawan laifukansu da taurin kansu ga manzanninsu. Allah ya bayyana cewa, ya yi wa Annabi (ﷺ) bayanin waɗannan abubuwa da ya haramta musu. Watau kamar yadda ya zo cikin *Suratul An'am*, aya ta 146. Allah ya bayyana cewa, bai zalunce su da wannan hukunci da ya yi musu ba, su ne dai suka zalunci kawunansu da yawan saɓa masa da hana mutane bin hanyarsa.
Sai kuma ya bayyana rahamarsa da karamcinsa ga masu saɓonsa cikin jahilci idan sun tuba sun koma gare shi sun gyara aikinsu, ya tabbatar musu cewa, zai yi musu gafara zai kuma ji ƙan su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Kuma mafi girman falalarsa shi ne wahayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa shugaban halittu gaba ɗaya Annabi Muhammadu (ﷺ) cewa, shi da al'ummarsa su bi addininsa.

2. Falalar wannan al'umma a kan sauran al'ummun da suka gabace ta.

Suratun Nahl (120-124)

إِنَّ إِبۡرَٰهِيمَ كَانَ أُمَّةٗ قَانِتٗا لِّلَّهِ حَنِيفٗا وَلَمۡ يَكُ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١٢٠ شَاكِرٗا لِّأَنۡعُمِهِۚ ٱجۡتَبَىٰهُ وَهَدَىٰهُ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ١٢١ وَءَاتَيۡنَٰهُ فِي ٱلدُّنۡيَا حَسَنَةٗۖ وَإِنَّهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١٢٢ ثُمَّ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ أَنِ ٱتَّبِعۡ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۖ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١٢٣ إِنَّمَا جُعِلَ ٱلسَّبۡتُ عَلَى ٱلَّذِينَ ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِۚ وَإِنَّ رَبَّكَ لَيَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ١٢٤

120. Lalle Ibrahimu ya zama abin koyi ne mai biyayya ga Allah mai kauce wa ɓarna, bai kuma zamanto daga masu shirka ba.

121. Mai godiya ne ga ni'imarsa (wato Allah), Ya zaɓe shi, Ya kuma shirye shi zuwa ga tafarki madaidaici.

122. Mun kuma ba shi kyakkyawa a duniya; lalle kuma shi a lahira tabbas yana daga cikin salihai.

123. Sannan Muka yi maka wahayi cewa, ka bi addinin Ibrahimu mai kauce wa ɓarna; bai kuwa zamanto daga masu shirka ba.

124. An farlanta (girmama ranar) Asabar kawai a kan waɗanda suka yi saɓani game da ita. kuma lalle Ubangijinka tabbas zai yi hukunci tsakaninsu ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna saɓani a game da shi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yabon bawansa kuma manzonsa badaɗayinsa Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda shi ne Limamin mabiya miƙaƙkiyar hanyar Tauhidi kuma Uban annabawa. Larabawan Kuraishawa suna riya cewa, su mabiya addininsa ne, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaryata su, ya kuma nisanta Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga hanyarsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabe shi da cewa shi mutum ne da ya tattara kyawawan halaye wanda ake koyi da halayensa, kuma mai dagewa ne a kan ɗa'ar Allah, ya kauce wa dukkan addinai ya rungumi Musulunci kaɗai, kuma bai taɓa zama daga mushirikai ba.
Kuma shi mai godiya ne a kan ni'imomin da Ubangijinsa ya yi masa. Allah ya zaɓe shi ya ba shi annabta ya kuma shiryar da shi zuwa madaidaiciyar hanya, ita ce bauta wa Allah shi kaɗai ba tare da shirka ba.
Allah kuma ya bayyana cewa, ya ba Annabi Ibrahimu kyakkyawa a nan duniya, watau annabci da kyakkyawan yabo daga al'umma. Sannan kuma a lahira yana cikin mutanen kirki waɗanda Allah ya tanadar musu gidajen Aljanna.
Sannan kuma Allah ya bayyana cewa, ya yi wa Annabi (ﷺ) wahayi da cewa, ya bi addinin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya ƙunshi Tauhidi da nesantar mushirikai da kira zuwa ga Allah da aiki da shari'arsa, ya kuma kauce wa duk wasu addinai in ban da addinin Musulunci kaɗai. Kuma ya ƙara tabbatar masa cewa, Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai taɓa kasancewa, ɗaya daga cikin mushirikai ba; shi mutum ne mai kaɗaita Allah da bauta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya soki tafarkin Yahudawa waɗanda suka sassaɓa a cikin lamarin addinin Allah. Haka kuma ya zaɓa wa kowace al'umma rana ɗaya daga cikin kwanakin mako wadda za su riƙa haɗuwa a cikinta suna bauta wa Allah. Ya bayyana cewa, ya wajabta wa Yahudawa girmama ranar Assabar ne bayan ya ba su damar su zaɓi Juma'a, amma sai suka kauce mata suka zaɓi ranar Assabar wadda suka ce ita ce kaɗai ranar da Allah bai halicci wata halitta a cikinta ba bayan ya gama halittu a ranar Juma'a. Daga lokacin da suka yi wannan zaɓin Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta musu yin aiki da shi a cikin shari'ar littafin Attaura na Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya kuma umarce su da su riƙe shi gam-gam, ya yi musu wasiyyar su bi Annabi Muhammadu (ﷺ) lokacin da Allah zai aiko shi, ya yi kuma alƙawari da su a kan haka. Suka ci gaba da riƙe wannan ranar ta Assabar har zuwa lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). An ce shi ne ya canja musu da ranar Lahadi. Wasu kuma sun ce Annabi Isa ya ci gaba da aiki da shari'ar Annabi Musa wadda ba a goge hukuncinta ba har zuwa lokacin da Allah ya ɗauke shi zuwa sama. To amma Nasara sai suka canja ranar zuwa Lahadi a zamanin Sarkin Rumawa Kusɗanɗinu domin su saɓa wa Yahudawa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mu ne na ƙarshe amma kuma na farko a ranar alƙiyama, sai dai kawai an riga ba su littafi. Sannan wannan ranar ta Juma'a ita ce ranar da aka farlanta musu sai suka sassaɓa a kanta, sai mu Allah ya nuna mana ita. Mutane duk bayanmu suke bi, Yahudawa gobe (Assabar) Nasara kuwa jibi (Lahadi)." [Bukhari #876 da Muslim #855].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) da Huzaifa (Allah ya ƙara masa yarda) suka ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah ya ɓatar da waɗanda suka gabace mu ba su gano Juma’a ba, Yahudawa suka ɗauki ranar Assabar, Nasara kuwa suka ɗauki ranar Lahadi. Sai mu kuma Allah ya kawo mu ya nuna mana ranar Juma’a. Sai ya jera su kamar haka: Juma’a sai Assabar sai Lahadi. To hakanan ma a lahira suna bayanmu, mu ne na ƙarshen zuwa a duniya, amma kuma na farko a ranar alƙiyama. Kuma mu ne za a fara yi wa hukunci a lahira kafin sauran halittu.” [Muslim #853, 856].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗora duk wani mai kira zuwa ga Allah a kan wasu matakai domin samun nasarar da’awarsa:
Mataki na farko, yin wa’azi da hikima. Hikima tana nufin la’akari da yanayin wanda ake kira ta fuskar ilimi da hankali da fahimta da miƙa wuya. Yana daga cikin hikima yin da’awa da ilimi ba da jahilci ba, da farawa da abin da ya fi muhimmanci, sannan mai bi masa, da farawa da abin da ya fi sauƙin fahimta. Yana daga cikin hikima haɗawa da tausasawa da bi a sannu. Idan ya miƙa wuya daga nan shi ke nan, idan bai gamsu ba sai a tafi zuwa ga mataki na biyu, shi ne:
Mataki na biyu, yin kyakkyawan wa’azi. Shi ne umarni da hani wanda yake ƙunshe da kwaɗaitarwa da tsoratarwa da lissafa amfanin da ke cikin bin umarni da bayanin cututtukan da ke cikin aikata abin da aka hana. Ko ta hanyar bayanin yadda Allah yake karrama mutanen da suka tsaya a kan koyarwar Musulunci da kuma yadda ƙarshen waɗanda suka yi wasa da addininsu ya kasance. Idan wanda ake kira yana ganin shi a kan gaskiya yake to sai a tafi zuwa:
Mataki na uku, watau jayayya ta hanya mafi kyau. Wannan yana nufin bin hanyar da za ta gamsar da hankalinsa da tunaninsa. Ya kafa masa hujja da abin da ya yarda ana kafa hujja da shi. Amma ba a yarda jayayyar nan ta kai ga husuma ko zage-zage ba, da har zai kai a rasa cim ma ainihin maƙasudin wannan tattaunawar.

2. Dole ne ramuwa ta kasance daidai da laifi. Duk wanda ya ƙara a kan haƙƙinsa to ya zama shi ne azzalumin.

3. Kwaɗaitarwa a kan yin afuwa da kau da kai. Kuma yin haka ya fi alheri a wurin Allah.

4. Falalar haƙuri a kan cutarwa.5. Allah yana tare da masu kiyaye dokokinsa da taikmakonsa.

Suratun Nahl (125-128)
ٱدۡعُ إِلَىٰ سَبِيلِ رَبِّكَ بِٱلۡحِكۡمَةِ وَٱلۡمَوۡعِظَةِ ٱلۡحَسَنَةِۖ وَجَٰدِلۡهُم بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُۚ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعۡلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِٱلۡمُهۡتَدِينَ ١٢٥ وَإِنۡ عَاقَبۡتُمۡ فَعَاقِبُواْ بِمِثۡلِ مَا عُوقِبۡتُم بِهِۦۖ وَلَئِن صَبَرۡتُمۡ لَهُوَ خَيۡرٞ لِّلصَّٰبِرِينَ ١٢٦ وَٱصۡبِرۡ وَمَا صَبۡرُكَ إِلَّا بِٱللَّهِۚ وَلَا تَحۡزَنۡ عَلَيۡهِمۡ وَلَا تَكُ فِي ضَيۡقٖ مِّمَّا يَمۡكُرُونَ ١٢٧ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّٱلَّذِينَ هُم مُّحۡسِنُونَ ١٢٨

125. Ka yi kira zuwa ga tafarkin Ubangiijnka cikin hikima da kyakkyawan wa’azi, ka kuma yi jayayya da su ta hanyar da ta fi kyau. Lalle Ubangijinka Shi ne Mafi sanin wanda ya ɓace daga hanyarsa, kuma Shi ne Mafi sanin shiryayyu.

126. Idan za ku yi uƙuba to ku yi uƙuba da kwatankwacin abin da aka yi muku uƙuba da shi. Kuma lalle idan kuka yi haƙuri to tabbas shi ne ya fi alheri ga masu haƙuri.

127. Kuma ka yi haƙuri, ba kuwa za ka iya haƙurin ba sai da taimakon Allah. Kada ranka ya ɓaci a kansu, kada kuma ka zama cikin ƙunci game da makircin da suke ƙullawa.

128. Lalle Allah Yana tare da waɗanda suka yi taƙawa da kuma waɗanda suke masu kyautatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya kira mutane zuwa ga addinin Musulunci ta hanyar hikima, watau la'akari da yanayin wanda ake kira da fahimtarsa da matsayinsa, ta hanyar kwaɗaitarwa da tsoratarwa. Ya kuma umarce shi da ya yi jayayya da wanda yake buƙatar sai an yi jayayya da shi amma jayayyar ta kasance ta hanyar da ta fi kyau. To amma shiryar da mutane su karɓi gaskiya wannan ba a hannunsa yake ba, shi abin da ya wajaba a kansa kawai shi ne isar da saƙon Allah. Allah shi ne mafi sanin wanda ya ɓace daga hanyar Musulunci, shi ne kuma mafi sanin shiryayyu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da adalci wajen ɗaukar fansa da neman haƙƙi. Allah ya yi umarni ga wanda zai rama wata uƙuba da aka yi masa, da ya rama daidai da irin yadda aka yi masa, kada ya zaƙe ya ƙara a kan abin da aka yi masa. Amma sai ya nuna cewa, mutane su yi haƙuri su yafe wa wanda ya yi musu ba daidai ba ya fi musu alheri a wurin Allah.

An karɓo daga Ubayyu ɗan Ka'abu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: A ranar yaƙin Uhudu an kashe Musulmi sittin mutanen Madina, a mutanen Makka da suka yi hijira kuma an kashe mutum shida, sai sahabban Manzon Allah (ﷺ) suka ce, duk sanda muka sake haɗuwa da mushirikai a rana irin wannan, muka kuma yi nasara a kansu, tabbas sai mun yi musu gunduwa-gunduwa. A ranar *Fathu Makka* sai wani sahabi ya ce: "Daga yau Kuraishawa sai labari." Sai mai shela ya yi shela yana cewa: Manzon Allah (ﷺ) ya amintar da baƙi da fari sai wane da wane - ya faɗi sunayen wasu mutane – to sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar har zuwa ƙarshenta. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Za mu yi haƙuri ba za mu rama ba." [Ahmad # da Tirmizi #3129].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi haƙuri a kan cutarwar da mushirikai suke yi masa, ya tabbatar masa cewa, babu mai datar da shi ga yin haƙuri sai Allah, don haka kada ya damu da bijirewar da kafirai suke yi masa, kuma kada ya zama cikin ƙunci saboda ƙulle-ƙullen makirci da suke yi, domin Allah ne mai taimakonsa kuma ya ishe shi komai. Ya kuma tabbatar masa da cewa, lalle yana tare da waɗanda suka kiyaye dokokinsa suka guji saɓa masa, da kuma waɗanda suke masu kyautatawa da yin ayyuka na ƙwarai. Allah zai taimaka musu ya ƙarfafe su cikin dukkan lamarinsu.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Isra'i shi ne tafiyar dare da aka yi da Annabi (ﷺ) daga Masallaci mai alfarma na Makka zuwa Massalcin Kudus gabanin hijira zuwa Madina da shekara ɗaya. Shi ne ayar ta ambata.
Mi'iraji kuwa shi ne hawa da Annabi (ﷺ) daga Masallacin Baitul Maƙadis har zuwa sama ta bakwai, daga nan har ya isa Magaryar tuƙewa inda ya riƙa jin sautin alƙalamin Kudura. Wannan shi ne bayanansa suka zo a hadisai masu yawa ingantattu.

2. Mafi yawancin malamai sun tabbatar da cewa an yi Isra'i ne da Annabi (ﷺ) da ruhinsa da gangar jikinsa kuma a farke ba a cikin barci ba, saboda dalilai kamar haka:
Na ɗaya, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe labarin da tasbihi wanda yakan kasance ne lokacin ambaton wani babban al'amari mai ban al'ajabi. Da a ce tafiyar a mafarki ne ya yi ta to da ba ta ƙunshi wani abin mamaki ba.
Na biyu, da a ce a barci ne da Kuraishawa ba su ƙaryata shi ba, domin irin wannan abu zai iya yiwuwa a mafarki.
Na uku, Allah ya ce: "Ya yi tafiyar dare da bawansa." Kalmar 'bawansa' ta ƙunshi duka ruhi da gangar jiki.
Na huɗu, hawan dabbar Buraƙa aiki ne da ya danganci gangar jiki ba ruhi ba.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Annabi (ﷺ) abubuwa masu girma da ban mamaki da ya halitta a sammai da ƙasa, ya nuna masa manya-manyan ayoyi da dangogin ilimi waɗanda shiga manyan makarantu da zama a gaban manya-manyan malamai kawai ba za su sa a san su ba. Allah ya yi masa waɗannan duka a cikin wani ɗan taƙaitaccen lokaci na dare.

17-Suratul Isra'i

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
A cikin Masahifu ana kiranta "*Suratul Isra'*". Sahabbai suna kiran ta "*Suratu Bani Isra'ila*", saboda a cikinta an bayar da labarin Banu Isra'ila.

An karƀo daga A'isha - Allah ya ƙara yarda da ita - ta ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya kasance ba ya barci har sai ya karanta '*Suratuz Zumar*' da '*Suratu Bani Isra'il*'." [Tirmizi#3405].
Hakanan Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya kira ta da Suratu *Bani Isra'il*. [Dubi Bukhari#4708].
Hakanan akan kira ta da suna *'Suratu Subhana*', saboda an buɗe ta da wannan kalma.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Wannan Sura *Makkiyya* ce, sai dai wasu malamai sun nuna cewa wasu ayoyi daga cikinta a Madina suka sauka, kamar aya ta (73) da ta (74). Wasu sun ƙara da aya ta (60). Wasu kuma sun ƙara aya ta (70) sun ce dukkansu *Madaniyya* ne. Wasu ma har sun haɗa da ayoyin wasiyyoyin da Allah ya yi, wato daga aya ta 23 har zuwa ta 38.
Amma Malam Ibn Ashur shi yana ganin ayoyinta gaba ɗaya saukarwar Makka ne, don haka shi a wajensa Sura ce *Makkiyya* zalla.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta hamsin (50) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan saukar '*Suratul Kasas*' gabanin '*Suratu Yunus*'.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Kufa ayoyinta ɗari da sha ɗaya ne (111), amma a lissafin mutanen Madina da Makka da Sham da Basra adadin ayoyinta ɗari da goma ne (110).

5. Babban Jigonta:
Babban jigonta shi ne magana a kan tabbatar da manzancin Annabi (ﷺ) da mu'ujizar Alƙur'ani da warware shubuhohin kafirai game da su, tare da tsokaci a kan Kaɗaitakar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai.

6. Daga Cikin Abubuwa da Ta Kunsa Akwai:
- Tabbatar da manzancin Annabi (ﷺ).
- Tabbatar da cewa Alƙur'ani wahayi ne daga Allah.
- Tabbatar da mu'ujizar Alƙur'ani.
- Tabbatar da Kaɗaitakar Ubangiji da cancantar a bauta masa ba tare da abokin tarayya ba.

• Mayar wa mushrikai martani game da sukan Alƙur’ani da suke yi, da bayanin cewa ba su ma fahimci abin da yake cikinsa ba.
• Tunatar da ɗan’adam ni’imomin da Allah ya yi masa, ko su kaɗai ya tsaya ya kalla zai fahimci Allah ne kaɗai ya cancanta ya bauta wa.
• Falalar shari’ar Musulunci, da kuma hikimar da take ƙunshe cikin addinin na Musulunci.
• Taɓo batun laifuffukan da suka sa Allah ya hallakar da al(Allah ya ƙara masa yarda) 'ummun da suka gabata.
• Bayanin wasu al’amura da suka shafi umarni da hani da kuma wasu ayyuka na ibada.

Suratul Isra’i (1)

سُبۡحَٰنَ ٱلَّذِيٓ أَسۡرَىٰ بِعَبۡدِهِۦ لَيۡلٗا مِّنَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِ إِلَى ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡأَقۡصَا ٱلَّذِي بَٰرَكۡنَا حَوۡلَهُۥ لِنُرِيَهُۥ مِنۡ ءَايَٰتِنَآۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ١

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Tsarki ya tabbata ga wanda Ya yi Isra’i da bawansa cikin dare daga Masallaci mai alfarma zuwa Masallaci mafi nisa (na Kudus) wanda Muka albarkaci kewayensa, don Mu nuna masa wasu daga ayoyinmu. Lalle Shi Mai ji ne, Mai gani.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da tsarkake kansa daga duk wata tawaya ko gajiyawa don ya nuna komai yana ƙarƙashin ikonsa, babu abin da zai gagare shi. Don haka ya yi bayanin tafiyar dare da ya yi da bawansa Annabi Muhammadu (ﷺ), watau Isra’i daga Masallaci mai alfarma na Makka zuwa Masallacin Baitul Maƙadis, wanda Allah ya albarkaci duk kewayensa da arzikin kayan marmari iri-iri da shuke-shuke da kayan amfanin gona, wanda yake kuma matattara ce ta annabawa. Allah ya yi masa wannan ne domin ya nuna masa manya-manyan ayoyi da shaidu a kan cikar ikonsa. Lalle kuwa Allah mai jin komai ne kuma mai ganin komai.
Hadisai da yawa sun tabbata daga Annabi (ﷺ) a kan bayanin wannan tafiya da aka yi da shi daga Masallacin Ka’aba zuwa Masallacin Kudus. Bayanin hadisan a dunƙule shi ne:
Wata rana Annabi (ﷺ) yana barci da daddare a ɗakin ‘yar’uwarsa Ummu Hani ‘yar Abu Ɗalib sai Mala’ika Jibrilu ya keto rufin ɗakin ya sauko, ya ɗauke shi zuwa Masallacin Ka’aba; a nan ne kuma ya buɗe ƙirjinsa ya wanke masa shi da ruwan Zamzam ya cika masa shi da hikima da imani, sannan ya rufe shi. Ya ɗauke shi zuwa ƙofar Masallaci inda aka zo da Buraƙa. Wata dabba ce fara, ta fi jaki amma ba ta kai alfadari ba, ya hau kanta, ta tafi da shi har sai da ya zo Masallacin Baitul Maƙadis, ya sauko daga kanta ya ɗaure ta a inda annabawa suke ɗaure dabbobinsu na hawa, sannan ya shiga cikin masallacin ya yi salla raka’a biyu. Sai ya fito, Mala’ika Jibrilu kuma ya kawo masa ƙwaryar giya da ta nono sai ya zaɓi ta nono, sai Jibrilu ya ce: “Ka dace da halitta ta asali, watau fiɗra.”
Daga nan Mala’ika Jibrilu ya hau da shi zuwa sama ta farko, inda ya haɗu da Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi masa sallama, shi kuma ya amsa masa ya yi masa maraba da ɗa nagari kuma Annabi nagari. Sai suka wuce sama ta biyu inda kuma ya haɗu da Annabi Yahya da Annabi Isa, waɗanda ‘ya’yan inna suke, su ma ya yi musu sallama suka amsa, suka kuma yi masa barka da ɗan’uwa na ƙwarai kuma Annabi na ƙwarai. Sai suka wuce sama ta uku inda suka haɗu da Annabi Yusuf; shi ma suka gaisa, ya yi masa barka da ɗan’uwa na ƙwarai kuma Annabi na ƙwarai. Daga nan suka wuce sama ta huɗu, a nan suka haɗu da Annabi Idris; shi ma suka gaisa, ya yi wa Annabi (ﷺ) barka da zuwa ya yi masa addu’a ta alheri. Sai kuma suka wuce sama ta biyar inda ya haɗu da Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ma suka gaisa ya yi masa fatan alheri. Sai kuma suka hau sama ta shida inda suka ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka gaisa da Manzon Allah ya yi masa maraba da

ɗan’uwa na ƙwarai kuma Annabi na ƙwarai, ya yi masa fatan alheri. Sai suka hau sama ta bakwai inda suka haɗu da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), shi ma suka gaisa, ya yi masa barka da zuwan ɗa na ƙwarai kuma Annabi na ƙwarai. Ya samu Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana zaune ya jingina da ɗakin Baitul Ma’amuri.
Shi wannan ɗaki ne na ibada wanda a kullum mala’iku dubu saba’in ne suke shigar sa, sannan in sun fito ba za su sake komawa ba har abada sai dai wasu sababbi. Sai kuma daga nan Manzon Allah ya wuce zuwa Magaryar tuƙewa (*Sidratul Muntaha*). Ita kuma Bishiya ce wadda faɗin ganyenta kamar kunnuwan giwaye suke, ‘ya’yanta kuwa kamar manyan kuloli ne, idan al’amarin Allah ya lulluɓe ta sai ta canja kamanninta nan take, babu mai iya siffanta kyawunta. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana da Annabi (ﷺ), a lokacin ne ya ba shi salloli hamsin shi da al’ummarsa. Daga nan Annabi (ﷺ) ya sauko har ya zo wajen Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai ya tambaye shi abin da Allah ya farlanta wa al’ummarsa, sai ya faɗa masa cewa, Allah ya farlanta musu salloli hamsin a kullum. Sai Annabi Musa ya ba shi shawara cewa, ya koma ya nemi sauƙi wurin Allah, domin shi ma ya gwada al’ummarsa Banu Isra’ila amma sun kasa. Annabi (ﷺ) ya karɓi wannan shawarar ya koma wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nemi sauƙi. Allah kuwa ya rage masa salloli biyar. Ya sauko har ya zo ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai ya sake ba shi shawarar ya koma wurin Allah ya nemi sauƙi domin al’ummarsa ba za su iya waɗannan salloli a kullum ba. Annabi (ﷺ) ya yarda ya sake komawa wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Allah ya sake rage masa salloli biyar. Ya sake dawowa wurin Annabi Musa. Haka suka yi ta yi da Annabi Musa har sai da sallolin nan suka koma biyar a kullum. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce wa Annabi (ﷺ): “Ya Muhammadu ga su nan salloli ne biyar a kullum dare da rana; kowace salla ɗaya a matsayin goma take, sun zama salloli hamsin ke nan.” Da Annabi (ﷺ) ya sake dawowa wurin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai ya sake ba shi irin waccan shawara ta baya, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Na yi ta komawa wurin Ubangijina har na fara jin kunyarsa.”
Daga nan sai Annabi (ﷺ) da Mala’ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka sauko zuwa Masallacin Baitul Maƙadis inda ya yi wa annabawa limancin salla. Sannan a ƙarshe ya wayi gari a Makka. Daga lokacin ya fara tunanin idan ya ba da labarin tafiyar nan tasa, to kafirai sun samu abin da za su yi ta yi masa izgili da shi suna ƙaryata shi a gaban jama’a.
Farkon wanda ya zo wurin Annabi (ﷺ) a wannan safiya daga cikin mushirikai shi ne Abu Jahali, ya tambaye shi, ko akwai wani sabon labari tare da shi? Annabi ya amsa masa cewa, e, akwai. Ya ce mene ne? Annabi ya kwashe duk labarin tafiyar ya faɗa masa. Abu Jahal cikin izgili ya ce wa Manzon Allah: “Baitul Maƙadis aka je da kai sannan kuma ka wayi gari a tsakaninmu?” Sai ya je ya gayyato wa Annabi jama’a don ya faɗa musu wannan labarin. Da Annabi ya zayyana musu duk abin da ya faru gare shi, sai wasu suka ƙaryata shi saboda nisan da suka sani wurin yana da shi. To sai suka nemi ya kwatanta musu wurin yadda yake don su tabbatar in da gaske yake yi ya je, sai kuwa ya siffanta musu shi sosai kamar yadda suka san shi. [Dubi, Bukhari #3207 da Muslim #164 da Ahmad #2819].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sau da yawa a Alƙur’ani Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana haɗa ambaton Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Muhammadu (ﷺ), kamar yadda yake haɗa ambaton Attaura da Alƙur’ani.

2. Godiya ga Allah siffa ce daga cikin siffofin manzannin Allah.

3. Malaman tarihi sun yi bayanin ɓarnar Banu Isra’ila guda biyu waɗanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata a waɗannan ayoyi. Hakanan sun yi bayanin mayaƙan da Allah zai ɗora a kan Banu Isra’ila a duk sanda suka yi ɓarnar. Masana tafsiri na farko sun haɗu a kan cewa, ɓarnar guda biyu da uƙubarsu

duka sun riga sun auku a tarihin Banu Isra'ila kafin zuwan Musulunci. Amma sun yi saɓani wajen tantance wane lokaci ne suka yi ɓarna ta farko da ta biyu, kuma su wane ne waɗannan bayin da Allah ya aiko don su zama uƙuba ga Banu Isra'ila? Mafi yawancin malaman tafsiri sun yarda da cewa, waɗanda aka aiko wa Banu Isra'ila bayan ɓarna ta farko su ne Jaluta da rundunarsa, suka yi wa Banu Isra'ila kisan wulaƙanci suka yi kaca-kaca da garuruwansu. Daga baya Allah ya sake ba wa Banu Isra'ila rinjaye a kansu, Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kashe Jaluta ƙarƙashin rundunar mayaƙan da Ɗaluta ya jagoranta, kamar yadda labarin ya zo cikin [*Suratul Baƙara*, aya ta 246-251].

A ɓarnarsu ta biyu kuwa, mafi yawan malaman tafsiri suna ganin mayaƙan da Allah ya aiko musu su ne mutanen Babila a ƙarƙashin jagorancin Bukhtanassar waɗanda su ma suka yi wa Banu Isra'ila kisan kiyashi suka yi rugu-rugu da gine-ginen Baitul Maƙadis suka kwashi ɓayi maza da mata daga cikin Banu Isra'ila.

4. Sunnar Allah ce da hikimarsa ya turo wa maɓarnata waɗanda za su hana su aikata ɓarna, domin hikimar Allah ta kawo gyara ta tabbata.

5. Gargaɗi ga waɗannan al'umma a kan guje wa saɓon Allah don gudun irin uƙubar da ta sami Banu Isra'la su ma ta same su, saboda sunnar Allah ɗaya ce, ba ta canzawa.

6. Nasarar da Banu Isra'ila suka riƙa samu a kan maƙiyansu a wani lokaci da nasarar da maƙiyansu suka riƙa samu a kansu a wani lokaci dalili ne wanda yake tabbatar da gaskiyar annabcin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Hakanan nasarar al'ummar Annabi Muhammadu (ﷺ) a kan maƙiyanta a wani lokaci da nasarar da maƙiyanta suke samu a kanta a wani lokaci, shi ma dalili ne daga cikin dalilan ingancin manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ).

Suratul Isra'i (2-8)

وَءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ وَجَعَلْنَٰهُ هُدًى لِّبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ أَلَّا تَتَّخِذُوا۟ مِن دُونِى وَكِيلًا ۝٢ ذُرِّيَّةَ مَنْ حَمَلْنَا مَعَ نُوحٍ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ عَبْدًا شَكُورًا ۝٣
وَقَضَيْنَآ إِلَىٰ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ فِى ٱلْكِتَٰبِ لَتُفْسِدُنَّ فِى ٱلْأَرْضِ مَرَّتَيْنِ وَلَتَعْلُنَّ عُلُوًّا كَبِيرًا ۝٤ فَإِذَا جَآءَ وَعْدُ أُولَىٰهُمَا بَعَثْنَا عَلَيْكُمْ عِبَادًا لَّنَآ
أُو۟لِى بَأْسٍ شَدِيدٍ فَجَاسُوا۟ خِلَٰلَ ٱلدِّيَارِ ۚ وَكَانَ وَعْدًا مَّفْعُولًا ۝٥ ثُمَّ رَدَدْنَا لَكُمُ ٱلْكَرَّةَ عَلَيْهِمْ وَأَمْدَدْنَٰكُم بِأَمْوَٰلٍ وَبَنِينَ وَجَعَلْنَٰكُمْ
أَكْثَرَ نَفِيرًا ۝٦ إِنْ أَحْسَنتُمْ أَحْسَنتُمْ لِأَنفُسِكُمْ ۖ وَإِنْ أَسَأْتُمْ فَلَهَا ۚ فَإِذَا جَآءَ وَعْدُ ٱلْءَاخِرَةِ لِيَسُۥٓـُٔوا۟ وُجُوهَكُمْ وَلِيَدْخُلُوا۟ ٱلْمَسْجِدَ كَمَا
دَخَلُوهُ أَوَّلَ مَرَّةٍ وَلِيُتَبِّرُوا۟ مَا عَلَوْا۟ تَتْبِيرًا ۝٧ عَسَىٰ رَبُّكُمْ أَن يَرْحَمَكُمْ ۚ وَإِنْ عُدتُّمْ عُدْنَا ۘ وَجَعَلْنَا جَهَنَّمَ لِلْكَٰفِرِينَ حَصِيرًا ۝٨

2. Kuma Mun bai wa Musa Littafi Muka kuma sanya shi ya zama shiriya ga Banu Isra'ila cewa: "Kada ku riƙi wani wakili ba ni ba."

3. (Ya ku) zurriyar waɗanda Muka ɗauko tare da Nuhu (a cikin jirgi). Lalle shi ya zamanto bawa ne mai yawan godiya.

4. Muka kuma ƙaddara ga Banu Isra'ila cikin Littafin (Attaura) cewa: "Lalle tabbas za ku yi ɓarna a bayan ƙasa sau biyu, kuma lalle tabbas za ku yi girman kai mai tsanani.

5. "To idan alƙawarin ta farkonsu (ɓarna) ya zo sai Mu aiko muku da bayinmu masu tsananin ƙarfi sai su kutsa tsakiyar gidajen (naku). Kuma (wannan) ya zamanto alƙawari ne mai faruwa.

6. “Sannan kuma Muka ba ku damar galaba a kansu, Muka kuma ƙare ku da dukiyoyi da ‘ya’ya, Muka kuma sanya ku kuka zama mafi yawan jama’a.

7. “Idan kun kyautata to kanku kuka kyautata wa, idan kuma kuka munana to kanku kuka yi wa. To idan alƙawarin (ɓarnar) ta ƙarshe ya zo (sai maƙiyanku su zo) don su wulaƙanta ku su kuma shiga masallaci (na Baitul Maƙadis) kamar yadda suka shige shi tun farko, kuma za su yi raga-raga da (duk) abin da suka biyo ta kansa.

8. “Mai yiwuwa ne Ubangijinku ya ji ƙan ku. (Amma) kuma idan kuka dawo (kan ɓarnar sai) Mu dawo (da azabtar da ku). Mun kuma sanya Jahannama ta zama shimfiɗa ga kafirai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin baiwar da ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) gabanin Annabi (ﷺ). Allah ya ba shi littafin Attaura wanda ya zamanto a lokacinsa mai shiryar da Banu Isra’ila, yana fitar da su daga duhun kafirci zuwa ga hasken imani. A cikinsa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗe su da kada su riƙi wani abin dogaro wanda za su riƙa mayar da al’amuransu gare shi ban da Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da su cewa, su ne fa zurriyar waɗanda ya kuɓutar a jirgin ruwa tare da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da Ɗufana ya cinye duniya. Don haka ya dace su tuna da wannan ni’imar da ya yi musu, su gode masa ta hanyar bauta masa shi kaɗai da bin umarninsa.
Sannan ya umarce su da su yi koyi da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wajen godiya ga Allah, domin shi Nuhu bawa ne na Allah mai yawan godiya gare shi.

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle Allah yana yarda da bawan da, idan ya ci abinci ko ya sha ruwa sai ya gode wa Allah ya yabe shi a kan haka.” [Muslim #2734 da Ahmad #11973].

Ya zo a cikin wani dogon hadisin ceto wanda Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ruwaito cewa: Annabi (ﷺ) ya ce: “…Mutane za su zo neman ceto wajen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) su ce: “Ya Nuhu, tabbas kai ne farkon manzanni zuwa mutanen duniya, kuma Allah ya sa maka sunan bawa mai godiya.” [Bukhari #4712].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cewa, Banu Isra’ila ba su yi aiki da nasihar da aka yi musu ba a cikin Attaura. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da su cewa, lalle tabbas za su yi ɓarna a bayan ƙasa har sau biyu, kuma lalle za su yi girman kai matuƙa da gaske wanda zai jefa su cikin zalunci da ta’addanci ga mutane.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa idan suka yi ɓarna ta farko to zai kawo wasu bayinsa masu tsananin ƙarfi ya ɗora su a kansu su yi ta karkashe su suna tarwatsa su, su kuma yi ta karakaina a tsakiyar gidajensu suna ɓata duk wani abu da suka biyo ta kansa. Allah ya tabbatar musu cewa, wannan alƙawari da ya yi tabbas sai ya faru gare su babu makawa.
Sai kuma ya faɗa musu cewa ya dawo musu da daularsu da ƙarfinsu har suka samu yin galaba a kan waɗancan maƙiyan nasu yayin da suka tuba suka koma ga Allah. Ya kuma ƙara musu yawan dukiyoyi bayan an wawashe musu tasu a baya, ya ƙara musu yawan ‘ya’ya bayan an kwashe musu ‘ya’yansu, wasu kuma an mayar da su bayi, ya ba su yawan adadin da ya fi na maƙiyansu.
Sannan ya gargaɗe su da cewa, idan sun kyautata sun bi Allah kansu suka yi wa. Idan kuma sun munana sun ɓata ayyukansu to don kansu, ba za su cuci Allah da komai ba. Ya tabbatar musu cewa, idan suka sake yin wata ɓarna a karo na biyu, to zai sake ɗora maƙiyansu a kansu don su sake dawowa cikinsu su wulaƙanta su wulaƙancin da sai ya bayyana a fili a fuskar kowa daga cikinsu, har ma kuma su shiga Baitul

Maƙadis su rushe shi kamar yadda suka shige shi a baya suka kuma rushe shi, kuma duk wani gari da suka yi galaba a kan mutanensa za su rushe shi kakaf.
Duk da haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna tausayinsa gare su, ya tabbatar musu da cewa, idan sun tuba, to zai ji ƙan su ya tausaya musu. To amma fa idan suka sake komawa ga ɓarna a karo na uku ko fiye da haka, to shi kuwa zai sake dawo musu da uƙubarsa, kuma a lahira ya sanya Jahannama ce makomar kafirai, da ita za a yi musu shimfiɗa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani littafi ne da ya ƙunshi mafi kyan hanyar shiriya, kuma mafi dacewar koyarwa ga duk wata buƙata ta ɗan'adam; wanda yake kuma nuna mafi kyan aƙidu da ibadu da kyawawan halaye da kyakkyawar mu'amala. Duk wanda ya riƙe shiriyar Alƙur'ani da karantarwarsa shi ne ya fi kowa kamala da adalci a rayuwarsa.

2. Ɗan'adam duk iliminsa yana tattare da jahiltar gaibunsa, don haka zai iya zaton cimma masalaharsa a cikin abin da yake cutarwa ce gare shi. Zai iya nacewa ga addu'a ta neman Allah ya ba shi wani abu wanda shi a tsammaninsa alheri ne a gare shi, alhalin kuwa sharri ne gare shi, amma bai sani ba saboda jahilcinsa da ruɗuwarsa da zahirin abubuwa.

3. Gaggawa da garaje ba abin yabo ne ba ga ɗan'adam.

Suratul Isra'i (9-11)
إِنَّ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانَ يَهْدِى لِلَّتِى هِىَ أَقْوَمُ وَيُبَشِّرُ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱلَّذِينَ يَعْمَلُونَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمْ أَجْرًا كَبِيرًا ۝٩ وَأَنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱلْءَاخِرَةِ أَعْتَدْنَا لَهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ۝١٠ وَيَدْعُ ٱلْإِنسَٰنُ بِٱلشَّرِّ دُعَآءَهُۥ بِٱلْخَيْرِ ۖ وَكَانَ ٱلْإِنسَٰنُ عَجُولًا ۝١١

9. Lalle wannan Alƙur'anin yana shiryarwa ne ga (hanya) mafi miƙewa, yana kuma yi wa muminai waɗanda suke yin kyawawan ayyuka albishir cewa, lalle suna da lada mai girma.

10. Waɗanda kuwa ba su yi imani da ranar lahira ba lalle Mun tanadar musu azaba mai raɗaɗi.

11. Kuma mutum yakan roƙi sharri kamar yadda yake roƙon alheri; mutum kuwa ya zamanto mai gaggawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falalar Alƙur'ani, inda ya ce lalle wannan Alƙur'ani da ya saukar wa Annabinsa Muhammadu (ﷺ) yana nuna wa mutane hanyar da ta fi kowace hanya kyau, ita ce hanyar addinin Musulunci da shari'arsa da koyarwarsa. Yana kuma yin albishir ga muminai waɗanda suka yi kyawawan ayyuka a duniya cewa, suna da wani gagarumin lada daga Allah a lahira. Sannan kuma ya ja kunnen waɗanda ba su yi imani da ranar alƙiyama ba cewa, ya yi musu tanadin mummunar azaba mai raɗaɗi a lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani hali na ɗan'adam wanda yake nuna jahilcinsa da garajensa, da cewa, shi ɗan'adam wani lokaci idan ya yi fushi yakan yi wa kansa ko 'ya'yansa ko dukiyarsa mummunar addu'a kamar yadda yake yin addu'a ta alheri ga kansa. Da kuwa a ce Allah zai amsa masa addu'arsa ne to da ya hallaka shi ko ya hallakar da dukiyarsa da 'ya'yansa. Allah ya tabbatar da cewa, shi ɗan'adam mutum ne mai gaggawa sosai.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kada ku yi wa kawunanku mummunar addu’a ko ku yi wa ‘ya’yanku ko ku yi wa hadimanku ko dukiyoyinku, don kada ku yi dace da lokacin da Allah yake baiwarsa ya amsa muku addu’arku.” [Muslim #3009 da Abu Dawud #1532].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sassaɓawar dare da rana ta wajen tsawo ko gajarta da maye gurbin juna da duhun dare da hasken rana, duka waɗannan dalilai ne na Kaɗaitakar Allah da samuwarsa da cikar iliminsa da ikonsa.

2. Kai-kawon dare da rana wata babbar ni’imar Allah ce ga ɗan’adam wadda ya wajaba ya riƙa yi masa godiya a kanta koyaushe.

Suratul Isra’i (12)

وَجَعَلْنَا ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ ءَايَتَيْنِۖ فَمَحَوْنَآ ءَايَةَ ٱلَّيْلِ وَجَعَلْنَآ ءَايَةَ ٱلنَّهَارِ مُبْصِرَةً لِّتَبْتَغُواْ فَضْلًا مِّن رَّبِّكُمْ وَلِتَعْلَمُواْ عَدَدَ ٱلسِّنِينَ وَٱلْحِسَابَۚ وَكُلَّ شَيْءٍ فَصَّلْنَٰهُ تَفْصِيلًا ١٢

12. Muka kuma sanya dare da rana su zama ayoyi guda biyu; sai Muka shafe ayar dare (ta zama duhu) Muka kuma sanya ayar rana ta zama mai haskakawa, don ku nemi falala daga Ubangijinku, don kuma ku san yawan shekaru da lissafi. Kowane abu kuwa Mun rarrabe shi filla-filla.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata babbar ni’ima da ya yi wa ɗan’adam kuma wadda take ƙunshe da wasu ayoyi masu nuna Kaɗaitakarsa da cikar Kudurarsa. Wannan ni’imar kuwa ita ce jujjuyawar dare da rana da sassaɓawarsu wajen tsawo da gajarta da sanyi da zafi. Ya yi dare mai duhu don ɗan’adam ya huta a cikinsa ya yi barci. Ya kuma sanya rana mai haske domin mutane su fita neman arzikinsu a ciki. Sannan kuma ta hanyar sassaɓawarsu ne mutane za su fahimci lissafin kwanaki da makwanni da watanni da shekaru da lokutan ibadunsu da wa’adin ƙulla mu’amalolinsu da juna. Allah ya bayyana cewa, ya yi bayanin komai filla-filla domin ya tantance mai gaskiya da marar gaskiya ya kuma ware ƙarya da gaskiya.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani ɗan’adam yana da littafin ayyukansa kyawawa da munana.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai cikakken adalci ne, don haka zai umarci bawansa ya karanta littafin ayyukansa da kansa, don ya tabbatar da laifukansa da kansa.

3. Duk ɗan’adam shi ne mai ɗaukar alhakin ayyukansa, idan ya yi aiki nagari don kansa, idan ya yi mummunan aiki ma don kansa, ba zai amfanar da Allah komai ba, ba kuma zai iya cutar da shi da saɓonsa ba.

4. Babu mai ɗauke wa wani laifinsa a ranar alƙiyama komai kusancinsa da shi ko kusancinsa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sai wanda Allah ya ga dama ya yafe masa.

5. Allah cikakken adali ne, don haka ba ya yi wa mutane azaba sai bayan saƙonsa ya same su ta hannun manzanninsa sannan suka bijire musu. Malamai sun kafa hujja da wannan ayar a kan cewa, mutanen da suka rayu kafin bayyanar Musulunci da ‘ya’yan mushirikai ba za a yi musu azaba a lahira ba kai-tsaye.

6. Fasiƙancin wasu da fajircinsu yakan iya zama sanadiyyar hallaka al’umma idan ba a samu masu umarni da kyakkyawa da hana mummuna a cikinsu ba.

7. Gargaɗi da razanarwa ga mushirikan wannan al’umma da nuna musu cewa, idan har Allah ya hallaka wasu al(Allah ya ƙara masa yarda) 'ummu da suka gabata saboda sun ƙaryata manzanninsu to su ma waɗannan masu ƙaryata Manzon Allah ba su fi waɗancan wata daraja ba a wurin Allah, su ne ma suka fi cancantar azabarsa, domin sun ƙaryata Manzon da ya fi dukkanin manzanni daraja a wurinsa.

Suratul Isra’i (13-17)

وَكُلَّ إِنسَٰنٍ أَلۡزَمۡنَٰهُ طَٰٓئِرَهُۥ فِي عُنُقِهِۦۖ وَنُخۡرِجُ لَهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ كِتَٰبٗا يَلۡقَىٰهُ مَنشُورًا ١٣ ٱقۡرَأۡ كِتَٰبَكَ كَفَىٰ بِنَفۡسِكَ ٱلۡيَوۡمَ عَلَيۡكَ حَسِيبٗا ١٤ مَّنِ ٱهۡتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهۡتَدِي لِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيۡهَاۚ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰۗ وَمَا كُنَّا مُعَذِّبِينَ حَتَّىٰ نَبۡعَثَ رَسُولٗا ١٥ وَإِذَآ أَرَدۡنَآ أَن نُّهۡلِكَ قَرۡيَةً أَمَرۡنَا مُتۡرَفِيهَا فَفَسَقُواْ فِيهَا فَحَقَّ عَلَيۡهَا ٱلۡقَوۡلُ فَدَمَّرۡنَٰهَا تَدۡمِيرٗا ١٦ وَكَمۡ أَهۡلَكۡنَا مِنَ ٱلۡقُرُونِ مِنۢ بَعۡدِ نُوحٖۗ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ بِذُنُوبِ عِبَادِهِۦ خَبِيرَۢا بَصِيرٗا ١٧

13. Kuma kowane mutum Mun ɗaura masa littafin aikinsa a wuyansa, za kuma Mu fito masa da wani littafi a ranar alƙiyama da zai same shi a buɗe.

14. (A ce da shi): “Karanta littafinka; a yau ka isa ka yi wa kanka hukunci da kanka.”

15. Wanda ya shiriya to lalle yana shiriya ne don kansa; wanda kuwa ya ɓata to lalle yana ɓata ne don kansa. Ba kuwa wanda zai ɗauki nauyin laifin wani. Kuma ba Mu zamanto Masu azabtarwa ba har sai Mun aiko da manzo.

16. Idan Muka nufi hallakar da wata alƙarya sai Mu sanya ‘yan ta-moren cikinta su aikata fasiƙanci a cikinta, sai kalmar azaba ta tabbata a kanta (watau alƙaryar) sai Mu rugurguza ta ragaraga.

17. Al’umma nawa ne Muka hallaka bayan Nuhu? Kuma ai ya isa Ubangijinka Ya zamana Mai cikakken sani ne da gani ga zunuban bayinsa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, aikin da duk wani ɗan’adam ya yi a nan duniya yana nan an kiyaye masa shi a littafin ayyukansa wanda mala’iku suke rubutawa da umarnin Allah, alheri ne ko sharri, sannan zai zo da shi rataye a wuyansa a ranar alƙiyama ba zai rabu da shi ba har sai an gama yi masa hisabi. Allah ya tabbatar masa cewa, zai fito masa da wannan littafi mai ƙunshe da duk ayyukansa kyawawa da munana a buɗe masa shi, kuma a umarce shi da ya karanta duk abin da yake ciki da kansa ya yi wa kansa hisabi a ranar.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa, shiriyar kowa da ɓatansa shi kaɗai ta shafa ba wani ba, don babu mai ɗaukar zunuban wani ko ya kawar masa su gwargwadon ƙwayar zarra, domin Allah cikakken adali ne babu wanda yake kamawa da laifi ya yi masa azaba sai bayan ya tsayar masa da hujja ta bakin manzanninsa sannan ya yi jayayya ya ƙaryata su. Amma idan ya miƙa wuya ya yi imani, ko hujjar ba ta je masa ba, to wannan Allah ba ya azabta shi.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilan da suke sa ya hallakar da wata al'umma ya gusar da ita daga bayan ƙasa, da cewa, duk lokacin da ya nufi hallakar da wata alƙarya saboda zaluncinsu sai ya ƙaddara wa 'yan ta-moren cikinta su saba wa umarninsa su keta dokokinsa, daga nan sai azabar Allah ta tabbata a kan wannan alƙarya, Allah ya rugurguza ta ragaraga.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, irin waɗannan al(Allah ya ƙara masa yarda) 'ummun da ya yi wa irin wannan azabar masu yawa ne, kuma duk ya hallaka su, watau kamar mutanen Annabi Nuhu da Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da sauransu; ya hallakar da su ne saboda kafircinsu da zaluncinsu. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa cewa, ya isa ya zamanto mai cikakken sani ne da ganin zunubban da bayinsa suke aikatawa, zai kuma yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk ƙoƙarin mutum wajen neman duniya ba zai same ta ba sai ƙarƙashin sharuɗɗa biyu. Na farko, zai sami gwargwadon abin da Allah ya ga damar ba shi ne, ba abin da shi yake so ba. Na biyu, sai idan Allah ya nufi ya ba shi; idan bai nufi ba shi abin da yake hanƙoron samu ba, to ba zai taba samun sa ba.

2. Kada mumini ya sanya duniya ce kaɗai a zuciyarsa ya manta da farkonsa da ƙarshensa.

3. Mutumin da zai ce yana son kyakkyawan sakamakon lahira amma ba ya aikin samun sa, to ruɗar kansa kawai yake yi. Duk abin da mutum yake son ya samu to dole ne sai ya yi fafutukar neman sa don ya cimma nasarar samun sa.

4. Arziki na duniya kaɗai ba shi yake nuna darajar bawa da matsayinsa a wurin Allah ba; Allah yana ba da duniya ga wanda yake so har ma da wanda ba ya so, amma ba ya bayar da imani sai ga wanda yake so.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara samuwar mutane a duniya cikin mabambanta yanayi; ya yi wani mawadaci wani talaka wani tsaka-tsaki; ya yi wani kyakkyawa wani mummuna wani kuma tsaka-tsaki; ya yi wani mai ilimi wani jahili wani kuma tsaka-tsaki; wani ya yi tsawon rai wani kuma ya mutu tun yana yaro.

Suratul Isra'i (18-21)

مَّن كَانَ يُرِيدُ ٱلۡعَاجِلَةَ عَجَّلۡنَا لَهُۥ فِيهَا مَا نَشَآءُ لِمَن نُّرِيدُ ثُمَّ جَعَلۡنَا لَهُۥ جَهَنَّمَ يَصۡلَىٰهَا مَذۡمُومٗا مَّدۡحُورٗا ١٨ وَمَنۡ أَرَادَ ٱلۡأٓخِرَةَ وَسَعَىٰ لَهَا سَعۡيَهَا وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَأُوْلَٰٓئِكَ كَانَ سَعۡيُهُم مَّشۡكُورٗا ١٩ كُلّٗا نُّمِدُّ هَٰٓؤُلَآءِ وَهَٰٓؤُلَآءِ مِنۡ عَطَآءِ رَبِّكَۚ وَمَا كَانَ عَطَآءُ رَبِّكَ مَحۡظُورًا ٢٠ ٱنظُرۡ كَيۡفَ فَضَّلۡنَا بَعۡضَهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖۚ وَلَلۡأٓخِرَةُ أَكۡبَرُ دَرَجَٰتٖ وَأَكۡبَرُ تَفۡضِيلٗا ٢١

18. Wanda ya kasance yana nufin duniya ne (kawai) to za Mu gaggauto masa a cikinta abin da Muka ga dama ga wanda Muka yi nufi; sannan Mu sanya masa Jahannama, ya shige ta (a lahira) yana abin zargi, korarre (daga rahamar Allah).

19. Wanda kuma ya nufi lahira ya kuma yi aiki irin nata dominta alhalin yana mumini, to waɗannan aikinsu ya zamanto abin godewa ne (a wurin Allah).

20. Dukkansu Muna wadata su ne da baiwar Ubangijinka; waɗannan da kuma waɗancan. Baiwar Ubangijinka kuwa ba ta zamo abar hanawa ba.

21. Dubi yadda Muka fifita wasunsu a kan wasu. Lalle kuwa lahira ita ta fi girman darajoji, kuma ta fi girman fifiko.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mutane sun kasu gida biyu:

Kashi na farko, su ne masu neman duniya da jin daɗinta mai gushewa, suka kuma yi ta aiki tuƙuru domin samun biyan buƙatarsu suka manta da farkonsu da ƙarshensu. To waɗannan Allah yana gaggauto musu da buƙatunsu na duniya gwargwadon yadda ya ga dama, kuma ga wanda ya riga ya rubuta wa hakan tun a Lauhul Mahfuzi. To amma fa wannan ɗan jin daɗi ne ƙanƙani, sannan a lahira Allah ya jefa shi wutar Jahannama yana abin zargi kuma korarre daga rahamar Allah, saboda ya zaɓi duniya ya kafirce wa Allah.
Kashi na biyu, su ne waɗanda lahira ce kawai a gabansu suka kuma yi aiki tuƙuru don samun sakamakonta, alhalin sun yi imani da shi. To waɗannan su ne aikinsu yake abin godewa a wurin Allah, zai karɓe shi ya taskace musu ladansa a wurinsa, don ya yi musu kyakkyawar sakayya a kansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk waɗannan kaso guda biyun babu wanda yake hana wa baiwarsa da kyautarsa a nan duniya; kowanne yana ba shi gwargwadon abin da ya riga ya ƙaddara masa zai samu a duniya.
Sannan ya nuna yadda ya halicci mutane mabambanta da fifiko a tsakaninsu, watau ya fifita wasu a kan wasu wajen arziki ko ilimi ko martaba. To amma ya nuna cewa, fifikon da ke lahira na ni'imar Aljanna ya fi girman darajoji ya kuma fi falala, don haka kowane mumini lalle ya yi ƙoƙarin samun irin wannan fifikon na lahira ba na duniya ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai ba tare da shirka ba ita ce kaɗai hanyar kuɓuta daga zargi da taɓewa duniya da lahira.

2. Haƙƙin Allah ne a bauta masa shi kaɗai, shi ne mafi girman haƙƙi da ke kan halittu baki ɗaya. Duk sauran haƙƙoƙi rassa ne na wannan babban haƙƙi.

3. Girman haƙƙin iyaye a kan 'ya'yansu, shi ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake gwama ambaton haƙƙin iyaye kai-tsaye bayan haƙƙin bauta masa shi kaɗai.

4. An umarci 'ya'ya su kasance ga iyayensu lokacin da suka tsufa suke neman taimako da kulawa kamar yadda su 'ya'yan suka kasance a gabansu lokacin yarintarsu da rauninsu, suka buƙaci raino da kulawa matuƙa daga iyayensu.

5. Wajibi ne 'ya'ya su girmama iyayensu su tausaya musu don neman lada daga wurin Allah, ba don tsoron su ko kwaɗayin wani abu a wurinsu ba.

6. Duk sanda tarbiyyar iyaye ga 'ya'yansu ta ƙaru to haka shi ma haƙƙin biyayya gare su yake ƙaruwa.

7. Hakanan duk mutumin da ya ba wa wani kyakkyawar tarbiyya a rayuwarsa ta addini ko ta rayuwar duniya, ko da ba iyayensa ba ne, to lalle yana da haƙƙin wannan tarbiyyar a kansa.

Suratul Isra'i (22-25)

لَّا تَجۡعَلۡ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتَقۡعُدَ مَذۡمُومٗا مَّخۡذُولٗا ٢٢ ۞وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلۡوَٰلِدَيۡنِ إِحۡسَٰنًاۚ إِمَّا يَبۡلُغَنَّ عِندَكَ ٱلۡكِبَرَ أَحَدُهُمَآ أَوۡ كِلَاهُمَا فَلَا تَقُل لَّهُمَآ أُفّٖ وَلَا تَنۡهَرۡهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوۡلٗا كَرِيمٗا ٢٣ وَٱخۡفِضۡ لَهُمَا جَنَاحَ ٱلذُّلِّ مِنَ ٱلرَّحۡمَةِ وَقُل رَّبِّ ٱرۡحَمۡهُمَا كَمَا رَبَّيَانِي صَغِيرٗا ٢٤ رَّبُّكُمۡ أَعۡلَمُ بِمَا فِي نُفُوسِكُمۡۚ إِن تَكُونُواْ صَٰلِحِينَ فَإِنَّهُۥ كَانَ لِلۡأَوَّٰبِينَ غَفُورٗا ٢٥

22. Kada ka haɗa wani abin bauta daban tare da Allah, sai ka zama abin zargi taɓaɓɓe.

23. Ubangijinka kuwa Ya hukunta cewa, kada ku bauta wa (wani) sai Shi kaɗai, kuma ku kyautatawa iyaye. Ko dai ya zamanto ɗayansu ne ya manyanta tare da kai, ko kuma dukkansu, to kada ka nuna ƙosawarka da su, kada kuma ka daka musu tsawa; ka yi musu magana ta girmamawa.

24. Ka kuma ƙasƙantar da kai gare su don tausayawa, ka kuma ce: "Ubangijina Ka ji ƙan su kamar yadda suka raine ni ina ɗan ƙarami."

25. Ubangijinku ne Mafi sanin abin da yake zukatanku. Idan kuka zamanto nagari, to lalle Shi Ya tabbata Mai gafara ne ga masu komawa gare Shi da tuba.

Daga aya ta 22 har zuwa ta 38 Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kafa wasu dokoki ne guda goma sha biyar waɗanda su ne rukunai na kyakkyawar rayuwa a duniya da samun babban rabo a lahira; kuma su ne za su tabbatar wa da 'yan'adam kyakkyawar zamantakewa a tsakaninsu.
Doka ta farko, ita ce kaɗaita Allah wajen bauta da guje wa bauta wa wani tare da shi a sama ko a ƙasa. Allah ya bayyana cewa, duk wanda ya riƙi wani abin bauta ba shi ba, to zai zama abin zargi daga Allah da mala'ikunsa da manzanninsa da mutanen ƙwarai, kuma zai zama taɓaɓɓe duniya da lahira. Don haka kada wanda ya bauta wa kowa sai shi. Watau a tsarkake shi da bauta shi kaɗai.
Sai kuma doka ta biyu, ya umarci mutum ya kyautata wa iyayensa, musamman ma lokacin da suka tsufa ko ɗayansu ya tsufa. Allah ya hana mutum ya yi wa iyayensa kowace irin magana da ke ɗauke da nuna ƙosawa ko gundura game da su, ballantana ma har ya kai ga daka musu tsawa ko ya yi musu baƙar magana. Sannan Allah ya umarce shi da ya yi musu magana ta girmamawa da mutuntawa.
Sai kuma ya umarce shi da ƙasƙantar da kai a gabansu tare da tausaya musu koyaushe, sannan ya yi ta yi musu addu'a yana roƙa musu rahamar Allah da gafararsa, suna da rai ne ko bayan sun mutu, saboda kyakkyawar tarbiyya da suka ba shi tun yana ƙarami.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa bayinsa cewa, ya fi kowa sanin abin da yake cikin zukatansu na tsarkake niyya wajen bauta masa ko wani aikin alheri, hakanan da wajen biyayyarsu ga iyaye, musamman idan ya zamanto suna da kyakkyawar niyya a zukatansu dangane da biyayyar da suke yi musu, ba kawai suna yi ne don tsoron su ba ko don kwaɗayin wani abu na maslaha daga gare su, to lalle Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gafarta wa waɗanda suka koma gare shi suka tuba daga duk wani abu na ƙosawa ko gajiyawa da zai fito daga gare su wanda ya danganci ɗa'a ga Allah ko biyayya ga iyayensu. Allah zai gafarta musu ya kuma yafe musu shi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Ya wulaƙanta, sannan ya wulaƙanta, sannan ya wulaƙanta, watau mutumin da ɗaya daga cikin iyayensa biyu ko duka biyun za su tsufa a gabansa, amma bai shiga Aljanna ba." [Muslim #2551].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haƙƙin makusantan mutum a dukiyarsa ya fi girma a kan waɗanda ba su ba, domin su suna da haƙƙi biyu ne; haƙƙin zumunci da kuma haƙƙin taimakon mabuƙaci.

2. Taimaka wa dangi makusanta abu ne da yake ƙara ƙarfafa danƙon zumunci a tsakanin dangin iyaye maza da iyaye mata, wanda haka yana ƙara haifar da haɗin kai da zaman lafiya a cikin ƙabila.

3. Taimaka wa mabuƙata da matafiyan da guzuri ya yanke musu yana ƙara haɗin kai da kyakkyawar zamantakewa a tsakanin 'ya'yan al'umma ɗaya.

4. Almubazzaranci, bayan kasancewarsa abu mai jawo fushin Allah, har ila yau hanya ce ta durƙushewar tattalin arzikin al'umma.

5. Abu ne mai kyau mumini ya riƙa roƙon Allah ya hore masa arzikin da zai taimaka wa mabuƙata da shi.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son tsakaitawa a cikin komai.

7. Arziki nufin Allah ne kamar yadda rashi ma nufinsa ne. Babu mai arzutawa ko ya talauta sai shi.

Suratul Isra'i (26-30)

وَءَاتِ ذَا ٱلۡقُرۡبَىٰ حَقَّهُۥ وَٱلۡمِسۡكِينَ وَٱبۡنَ ٱلسَّبِيلِ وَلَا تُبَذِّرۡ تَبۡذِيرًا ٢٦ إِنَّ ٱلۡمُبَذِّرِينَ كَانُوٓاْ إِخۡوَٰنَ ٱلشَّيَٰطِينِۖ وَكَانَ ٱلشَّيۡطَٰنُ لِرَبِّهِۦ كَفُورٗا ٢٧ وَإِمَّا تُعۡرِضَنَّ عَنۡهُمُ ٱبۡتِغَآءَ رَحۡمَةٖ مِّن رَّبِّكَ تَرۡجُوهَا فَقُل لَّهُمۡ قَوۡلٗا مَّيۡسُورٗا ٢٨ وَلَا تَجۡعَلۡ يَدَكَ مَغۡلُولَةً إِلَىٰ عُنُقِكَ وَلَا تَبۡسُطۡهَا كُلَّ ٱلۡبَسۡطِ فَتَقۡعُدَ مَلُومٗا مَّحۡسُورًا ٢٩ إِنَّ رَبَّكَ يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقۡدِرُۚ إِنَّهُۥ كَانَ بِعِبَادِهِۦ خَبِيرَۢا بَصِيرٗا ٣٠

26. Kuma ka bai wa makusanci haƙƙinsa, da miskini da matafiyi, kada kuma ka yi kowane irin almubazzaranci.

27. Lalle masu almubazzaranci sun tabbata dangin shaiɗanu; Shaiɗan kuwa ya zamanto mai yawan kafirce wa Ubangijinsa ne.

28. Idan kuwa ka kau da kanka daga gare su don neman wata rahama daga Ubangijinka da kake sa ran samun ta, to sai ka yi musu magana mai daɗi.

29. Kada kuma ka ƙuƙunce hannunka a wuyanka (ka ƙi yin kyauta), kada kuma ka shimfiɗa shi gaba ɗaya (watau ka saki komai), sai ka wayi gari abin zargi (saboda rowa), mai nadama (saboda almubazaranci).

30. Lalle Ubangijinka Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, kuma Yana ƙuntatawa (ga wanda Ya ga dama). Lalle Shi Ya tabbata Masani ne, Mai ganin bayinsa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana dokokin shari'arsa waɗanda kulawa da su ne zai lamunce wa ɗan'adam kyakkyawar rayuwa duniya da lahira. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasiyya ta uku, watau ba wa dangi makusanta haƙƙinsu na taimako da sada zumunci da girmamawa ga kowanne gwargwadon kusancinsa. Wasiyya ta huɗu ita ce, ba wa mabuƙaci wanda ba ɗan'uwa na jini ba haƙƙinsa, shi ma na taimako da tausayawa daga dukiyar zakka da wadda ba

ta zakka ba. Wasiyya ta biyar ita ce, taimakon matafiyi wanda guzurinsa ya yanke masa da abin da zai kai shi garinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kashedi ga yin almubazzaranci da dukiya; wannan ita ce doka ta shida. Almubazzaranci shi ne kashe dukiya inda bai dace ba ko da kuwa kaɗan ce. Allah ya bayyana illar yin haka da cewa, masu almubazzaranci suna kashe dukiyoyinsu wurin saɓon Allah da ta hanyar da ba ta kamata ba, waɗannan 'yan'uwan shaiɗanu ne, domin su suke yi wa biyayya ba Allah ba. Shaiɗan kuwa da ma shi mai butulci ne ga Ubangijinsa, babu abin da yake aikatawa sai saɓon Allah, ba kuma ya yin umarni da wani abu sai abin da zai fusata Ubangijinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana yadda mutum ya dace ya yi yayin da masu neman wani taimako daga gare shi suka zo, amma kuma ba shi da abin da zai taimaka musu; shi ma yana jiran Allah ya hore masa, to kamata ya yi ya faɗa musu magana mai daɗi, kamar yi musu addu'ar Allah ya hore musu ko kuma yi musu alƙawarin taimaka musu duk lokacin da Allah ya hore.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sifanta yadda mutum ya kamata ya zama tsaka-tsaki wajen sarrafa dukiyarsa, watau kada ya kame hannunsa ya yi rowa da ita, ya ƙi taimaka wa waɗanda ya dace ya taimaka musu; kada kuma ya saki hannunsa wajen kashe dukiyarsa har ya bayar da abin da ya fi ƙarfin dukiyar. Domin kuwa yin rowa zai jawo masa zargi da suka daga mutane; wuce iyaka kuma wajen kashe kuɗi zai haifar masa durƙushewa har ya wayi gari ba abin da zai taimaka da shi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kullum idan gari ya waye mala'iku biyu suna saukowa daga sama, ɗayansu yana cewa,: "Ya Allah, ka mayar wa da mai ciyar da dukiyarsa makwafin abin da ya ciyar." Ɗayan kuma yana cewa,: "Ya Allah, ka lalata dukiyar wanda ya yi rowa." [Bukhari #1442 da Muslim #1010].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, arziki yana hannunsa ne yana yalwata shi ga wanda ya ga dama, yana kuma ƙuntata shi ga wanda ya ga dama saboda wata hikima da shi ya fi sanin ta. Lalle Allah mai cikakken sanin bayinsa ne mai ganin duk ayyukansu ne babu abin da yake ɓuya gare shi, don haka yake sarrafa su yadda ya ga dama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin kashe 'ya'ya saboda tsoron talauci. Wannan ya ƙunshi masu tsayar da haihuwa gaba ɗayanta don gudun ɗaukar nauyin iyali.

2. Haramcin kusantar zina. Wannan ya ƙunshi haramcin aikata duk wani abu da kan iya jawo aukuwar zinar, kamar cakuɗuwar maza da mata da kallon tsiraici da makamantansu.

3. Haramcin kashe rai ba da wani haƙƙi ba. Wannan ya ƙunshi duk wani rai na ɗan'adam namiji ko mace babba ne ko yaro, Musulmi ne ko kafiri.

4. Zartar da ƙisasi, watau ramuwa ko afuwa ga wanda ya yi kisan ganganci, haƙƙin waliyyan wanda aka kashe ne. Babu wanda zai sha gabansu a wannan haƙƙin duk matsayinsa da ikonsa.

5. Haƙƙi ne na waliyyin wanda aka kashe a taimaka masa har ya kai ga samun haƙƙinsa daga wanda ya yi kisa.

6. Haramcin kusantar dukiyar maraya da nufin ɓarna ko cutarwa. Amma ya halatta a yi masa kasuwanci da ita har zuwa lokacin da zai mallaki hankalinsa sai a ba shi kayansa.

7. Wajabcin cika alƙawarin da bawa ya ɗauka.

Suratul Isra'i (31-34)

وَلَا تَقْتُلُوٓاْ أَوْلَٰدَكُمْ خَشْيَةَ إِمْلَٰقٍ ۖ نَّحْنُ نَرْزُقُهُمْ وَإِيَّاكُمْ ۚ إِنَّ قَتْلَهُمْ كَانَ خِطْـًٔا كَبِيرًا ﴿٣١﴾ وَلَا تَقْرَبُواْ ٱلزِّنَىٰٓ ۖ إِنَّهُۥ كَانَ فَٰحِشَةً وَسَآءَ سَبِيلًا ﴿٣٢﴾ وَلَا تَقْتُلُواْ ٱلنَّفْسَ ٱلَّتِى حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلْحَقِّ ۗ وَمَن قُتِلَ مَظْلُومًا فَقَدْ جَعَلْنَا لِوَلِيِّهِۦ سُلْطَٰنًا فَلَا يُسْرِف فِّى ٱلْقَتْلِ ۖ إِنَّهُۥ كَانَ مَنصُورًا ﴿٣٣﴾ وَلَا تَقْرَبُواْ مَالَ ٱلْيَتِيمِ إِلَّا بِٱلَّتِى هِىَ أَحْسَنُ حَتَّىٰ يَبْلُغَ أَشُدَّهُۥ ۚ وَأَوْفُواْ بِٱلْعَهْدِ ۖ إِنَّ ٱلْعَهْدَ كَانَ مَسْـُٔولًا ﴿٣٤﴾

31. Kada kuma ku kashe 'ya'yayenku don tsoron talauci: Mu ne Muke arzuta su har ma da ku. Lalle kashe su kuskure ne babba.

32. Kuma kada ku kusanci zina; lalle ita (zina) ta kasance mugun aiki ne, kuma hanya ce wadda ta munana.

33. Kuma kada ku kashe ran da Allah Ya haramta (kashewa) sai da haƙƙi. Wanda aka kashe ta hanyar zalunci, to lalle Mun bai wa magajinsa dama (ta ramuwa), to (amma) kada ya wuce gona da iri wajen kisa; lalle shi ya zamanto abin dafa wa baya ne.

34. Kuma kada ku kusanci dukiyar maraya sai dai ta (hanya) wadda take mafi kyau, har sai ya kawo ƙarfi. Kuma ku cika alƙawari; lalle alƙawari ya kasance abin tambaya ne (a lahira).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana dokokin nan na shari'arsa. Ya ambaci doka ta bakwai, watau hani a kan kashe 'ya'ya saboda tsoron talauci. Ya tabbatar wa da iyaye cewa, shi ne mai ciyar da su ya shayar da su da sauran buƙatunsu; su ma iyayen shi ne mai arzuta su. Ya yi kashedi da cewa, kashe 'ya'ya saboda wannan dalili ba ƙaramin laifi ne ba; yana daga cikin manyan laifuka waɗanda suka shafi rashin tausayi da rashin imani, domin babu wani dalilin kashe su sam-sam.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa,: "Wane zunubi ne ya fi girma?" Sai ya ce: "Ka sanya wa Allah kishiya alhalin shi ne ya halicce ka." Sai na ce: "Sai kuma wanne?" Sai ya ce: "Ka kashe ɗanka don kada ya ci tare da kai." Na ce: "Sai kuma me?" Sai ya ce: "Ka yi zina da matar maƙocinka." [Bukhari #4477 da Muslim #86].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci doka ta takwas, ita ce hani a kan kusantar zina, watau nesantar duk wani abu da zai taimaka a kan aukuwar zina. Ya tabbatar da cewa, munin zina ya kai matuƙa sosai, kuma hanya ce mummuna mai kaiwa ga azabar Allah Ta'ala.

An karɓo daga Abu Umamata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wani matashi ya zo wajen Annabi (ﷺ) ya ce: "Ka ba ni izinin aikata zina." Sai jama'a suka yiwo kansa suna kwaɓar sa, suna ce masa ya yi shiru kada ya ƙara faɗar wannan ɗanyar maganar. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce da shi: "Matso kusa." Sai ya matsa dab da Manzon Allah (ﷺ), sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "To zauna." Sai ya zauna. Sai ya ce masa: "Kana son a yi zina da mahaifiyarka?" Ya ce: "A'a wallahi. Allah ya sanya ni fansa gare ka." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "To mutane ma ba sa son a yi zina da iyayensu mata." Sai kuma ya ce masa: "Kana so a yi zina da 'yarka?" Ya ce: "A'a wallahi, ya Manzon Allah. Allah ya sanya ni fansa gare ka." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "To hakanan ma mutane ba sa son a yi da 'ya'yansu mata." Sai ya ce masa: "Kana so a yi da gwaggonka?" Sai ya ce: "A'a wallahi. Allah ya sanya ni fansa gare ka." Sai ya ce masa: "To mutane ma ba sa so a yi zina da gwaggonninsu." Sai ya ce: "Kana so a yi da innarka?" Sai ya ce: "A'a wallahi. Allah ya sanya ni fansa a gare ka." Sai Manzon Allah ya ce masa: "To hakanan mutane ma ba sa

son a yi da innoninsu.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ɗora masa hannu a jikinsa ya ce: “Ya Allah ka gafarta masa zunubinsa, ka tsarkake zuciyarsa, ka tsare farjinsa.” Daga rannan wannan saurayi bai ƙara waiwayen wani abu irin wannan ba.” [Ahmad, Musnad #22211].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci doka ta tara, ita ce hani a kan kisan wani rai ba tare da haƙƙi ba na ridda ko ƙisasi ko haddin zina.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Jinin mutum Musulmi wanda yake shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah kuma lalle ni Manzon Allah ne, bai halatta ba, sai saboda ɗayan abubuwa uku: Mazinacin da ya taɓa yin aure da wanda ya kashe rai da wanda ya bar addini ya rabu da jama’ar Musulmi.” [Muslim #1676 da Ahmad #3621].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hurumin neman fansa ta ƙisasi ko diyya ga wanda aka kashe ɗan’uwansa na jini bisa zalunci. Allah ya bayyana cewa, ya bai wa ɗan’uwansa hujja ƙarara a hannunsa ta ya nemi sakayya ga ɗan’uwansa, a yi ƙisasi idan kowa ya amince daga dangi, ko ya karɓi diyya. Ya kuma hana ya wuce gona da iri wajen ɗaukar fansa, watau ya kashe wanda ba shi ya yi kisan ba, ko ya yi gunduwa-gunduwa da shi bayan an kashe shi. Shi wannan ɗan’uwa na wanda aka kashe wanda za a taimaka wa ne har ya kai ga cimma burinsa na karɓo haƙƙin jinin ɗan’uwansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana doka ta goma, watau hana cin dukiyar maraya, wanda mahaifinsa ya rasu ya bar shi bai balaga ba. To shi ma haramun ne mutum ya ci dukiyarsa ko ya salwantar masa da ita don an danƙa ta a hannunsa. Sai dai an yarje masa ya haɓaka masa ita ta hanyar kasuwanci da sana’a har lokacin da zai mallaki hankalinsa, sai ya mayar masa da dukiyarsa.
Ya zo a cikin [Sahihu Muslim #1826], Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda): “Ya Aba Zarrin, lalle ni na gan ka kai mai rauni ne, kuma ni ina so maka abin da nake so wa kaina, don haka kada ka shugabanci ko da mutum biyu ne, kada kuma ka ɗauki nauyin kula da dukiyar maraya.”
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da cika alƙawari. Wannan ita ce doka ta sha ɗaya. Alƙawari ya haɗa har da wanda yake tsakanin bawa da Ubangijinsa na bauta masa shi kaɗai ba tare da shirka ba, da kuma wanda yake tsakanin mutum biyu ko fiye. Su cika ba tare da sun rage komai ba ko sun warware shi. Ya kuma gargaɗe su da cewa, tabbas a ranar lahira sai ya tambaye su game da alƙawuransu sun cika ko ba su cika ba?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin cika mudu da daidaita sikeli wajen awo. Wannan ya haɗa har da hana duk wani algus a harkar saye da sayarwa da sana’o’in hannu, da kuma yin umarni da gaskiya wajen mu’amala da juna.

2. Haramcin bibiyar abin da mutum ba shi da wani sani a kansa, da yin magana a addini ba da ilimi ba.

3. Lalle bawa ya riƙa tunawa cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai tambaye shi a kan duk wasu gaɓoɓinsa, kuma ya tanadi irin amsar da zai bayar a gaban Allah.

4. Haramcin yin taƙama da nuna isa yayin tafiya.<p style=(Allah ya ƙara masa yarda) "text-align:center(Allah ya ƙara masa yarda)

Suratul Isra'i (35-39)

وَأَوۡفُواْ ٱلۡكَيۡلَ إِذَا كِلۡتُمۡ وَزِنُواْ بِٱلۡقِسۡطَاسِ ٱلۡمُسۡتَقِيمِۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ وَأَحۡسَنُ تَأۡوِيلٗا ٣٥ وَلَا تَقۡفُ مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٌۚ إِنَّ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡبَصَرَ
وَٱلۡفُؤَادَ كُلُّ أُوْلَٰٓئِكَ كَانَ عَنۡهُ مَسۡـُٔولٗا ٣٦ وَلَا تَمۡشِ فِي ٱلۡأَرۡضِ مَرَحًاۖ إِنَّكَ لَن تَخۡرِقَ ٱلۡأَرۡضَ وَلَن تَبۡلُغَ ٱلۡجِبَالَ طُولٗا ٣٧ كُلُّ ذَٰلِكَ كَانَ
سَيِّئُهُۥ عِندَ رَبِّكَ مَكۡرُوهٗا ٣٨ ذَٰلِكَ مِمَّآ أَوۡحَىٰٓ إِلَيۡكَ رَبُّكَ مِنَ ٱلۡحِكۡمَةِۗ وَلَا تَجۡعَلۡ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتُلۡقَىٰ فِي جَهَنَّمَ مَلُومٗا مَّدۡحُورًا ٣٩

35. Kuma ku cika mudu idan kuka yi awo, kuma ku auna nauyi da ma'auni na adalci. Wannan (shi ya fi) alheri ya kuma fi kyakkyawan ƙarshe.

36. Kada kuma ka dinga bibiyar abin da ba ka da ilimi a kansa. Lalle ji da gani da kuma tunani duk waɗannan sun zama abin tambaya ne game da su.

37. Kada kuma ka yi tafiya a bayan ƙasa kana mai girman kai; lalle kai ba za ka tsaga ƙasa ba (don ƙasaita) kuma ba za ka kai tsawon duwatsu ba.

38. Duk waɗancan abubuwa mummunansu a wurin Ubangijinka abin ƙi ne.

39. Wannan yana daga cikin abin da Ubangijinka Ya yiwo maka wahayi da shi na hikima. Kada kuma ka sanya wani abin bauta tare da Allah, sai a jefa ka a cikin Jahannama kana abin zargi, korarre (daga rahama).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana dokokinsa da wasiyyoyinsa da ya yi wa bayinsa guda goma sha biyar. A wasiyya ta goma sha biyu da ta sha uku, ya yi wa mutane umarni da cika mudu yayin da suke auna wa wasu, kada su tauye musu komai na haƙƙinsu, ya kuma umarce su da daidaita sikeli bisa gaskiya da adalci, kada su yi dabarar rage wa mutane haƙƙoƙinsu. Ya nuna musu cewa, wannan cika ma'aunin da tsayar da sikelin shi ne alheri gare su duniya da lahira.
Sai kuma ya ambaci doka ta sha huɗu wadda ta ƙunshi hani game da kutsawa cikin abin da mutum ba shi da wani ilimi a kansa; ya bi labarin da bai tabbatar da sahihancinsa ba. Allah ya tsoratar da mai aikata haka, ya bayyana cewa sai an titsiye shi ranar alƙiyama an yi masa tambaya game da yadda ya yi amfani da jinsa da ganinsa da zuciyarsa, a alheri ne ya yi amfani da su ko a wajen sharri ne, kuma a yi masa sakayyar da ta dace da aikinsa.
Malam Katada ya ce: Ma'anar ayar: "Kada ka ce: Na gani, alhalin ba ka gani ba, ko ka ce: Na ji, alhalin ba ka ji ba, ko ka ce: Na sani, alhalin ba ka sani ba; duk waɗannan sai Allah ya tambaye ka a kansu" [Ibn Kasir, juzi na 5, shafi na 75].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana mumini yin tafiya irin ta ƙasaita da girman kai da taƙama a bayan ƙasa, domin duk inda ya kai ga nuna isa da ƙasaita bai isa ya tsaga ƙasa da tafiyarsa ba, kuma ɗaga kai da tsawonsa ba zai kai na duwatsu ba, don haka bai isa komai ba a wurin Allah. Wannan ita ce doka ta sha biyar.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wani mutum yana cikin tafiya ya caɓa ado yana jiji da kansa ya taje sumarsa sai kawai Allah ya nufi ƙasa ta haɗiye shi, yana nan yana ta gangarawa a cikinta har ranar tashin alƙiyama." [Bukhari #5789 da Muslim #2088].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, duk waɗannan munanan ayyuka da aka ambata a ayoyin da suka gabata, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai taɓa amincewa da ɗaya daga cikinsu ba, sai ya kama duk wanda ya aikata su kuma ya azabtar da shi a kai.

Sannan ya nuna cewa, duk abubuwan da ya yi umarni da su da waɗanda ya hana suna daga cikin abubuwan da ya yi wa Manzonsa (ﷺ) wahayinsu na hukunce-hukunce. Sai a ƙarshe ya sake jaddada haninsa ga ɗan'adam da kada ya riƙi wani abin bauta tare da Allah; idan ya yi haka kuwa to ranar alƙiyama za a jefa shi cikin wutar Jahannama yana abin zargi a wurin Allah da bayinsa na ƙwarai, yana kuma korarre daga rahamar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin munin jingina wa Allah 'ya'ya mata.

2. Alƙur'ani ya ƙunshi fuskoki daban-daban na faɗakarwa da ba da labaran al(Allah ya ƙara masa yarda) 'ummun da suka shuɗe da bayanin hukunce-hukunce da bayanin sakamakon lahira na ni'ima ko na azaba da bayar da misalai iri-iri don kusanto da fahimta.

3. Yawancin mutane sun fi karkata ga ƙarya a kan gaskiya, don haka babu abin da ayoyin Allah suke ƙara musu sai bijirewa da nisantar gaskiya.

4. Tabbatar da Kaɗaitar Allah.

5. Babu wani mahaluƙi a sama ko a ƙasa face yana yi wa Allah tasbihi, don haka idan ɗan'adam ya bijire wajen yi wa Allah tasbihi ba zai cuci kowa ba sai dai kansa.

6. Tabbatar wa da Allah sunayen 'Mai haƙuri' da 'Mai gafara', da kuma tabbatar masa siffar haƙuri da ta gafara.

Suratul Isra'i (40-44)

أَفَأَصۡفَىٰكُمۡ رَبُّكُم بِٱلۡبَنِينَ وَٱتَّخَذَ مِنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ إِنَٰثًاۚ إِنَّكُمۡ لَتَقُولُونَ قَوۡلًا عَظِيمٗا ٤٠ وَلَقَدۡ صَرَّفۡنَا فِي هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ لِيَذَّكَّرُواْ وَمَا
يَزِيدُهُمۡ إِلَّا نُفُورٗا ٤١ قُل لَّوۡ كَانَ مَعَهُۥٓ ءَالِهَةٞ كَمَا يَقُولُونَ إِذٗا لَّٱبۡتَغَوۡاْ إِلَىٰ ذِي ٱلۡعَرۡشِ سَبِيلٗا ٤٢ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يَقُولُونَ عُلُوّٗا
كَبِيرٗا ٤٣ تُسَبِّحُ لَهُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ ٱلسَّبۡعُ وَٱلۡأَرۡضُ وَمَن فِيهِنَّۚ وَإِن مِّن شَيۡءٍ إِلَّا يُسَبِّحُ بِحَمۡدِهِۦ وَلَٰكِن لَّا تَفۡقَهُونَ تَسۡبِيحَهُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ حَلِيمًا
غَفُورٗا ٤٤

40. Shin yanzu kuwa Ubangijinku Ya zaɓar muku 'ya'ya maza ne (Shi) kuwa Ya ɗauki ('ya'ya) mata daga mala'iku? Lalle ku tabbas kuna faɗar babbar magana.

41. Haƙiƙa kuma Mun bayyana (hujjoji) a cikin wannan Alƙur'ani don su wa'azantu, (amma) kuma ba abin da yake ƙara musu sai nesanta (daga gaskiya).

42. Ka ce (da su): "Da dai akwai wasu alloli tare da shi (Allah), kamar yadda suke da'awa, to kuwa da sun nemi hanyar (yin hamayya) da Mai Al'arshi (watau Allah)."

43. Tsarki ya tabbata gare Shi, kuma Ya ɗaukaka ɗaukaka mai girma game da abin da suke faɗa.

44. Sammai bakwai da ƙasa da abin da yake cikinsu (duka) suna tsarkake Shi. Ba wani abu wanda ba ya tasbihi tare da gode masa, sai dai ba kwa fahimtar tasbihinsu. Lalle Shi Ya kasance Mai yawan haƙuri ne, Mai yawan gafara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kakkausar suka ga mushirikai masu cewa wai Allah yana da ‘ya’ya mata su ne mala’iku, ya bayyana cewa, wannan maganar da suke yi ta yi muni matuƙa. Su suna ƙyamar a danganta musu ‘ya’ya mata suna kuma ɗaukan hakan a matsayin tawaya, to ta yaya za a ce, su ya zaba musu ‘ya’ya maza, shi kuma ya riƙe ‘ya’ya mata? Wannan maganar tasu babu shakka rashin girmamawa ce ƙarara ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Allah kuma ya bayyana cewa, ya sarrafa wa bayinsa ayoyin Alƙur’ani ta fuskoki daban-daban; ya kawo musu hukunce-hukunce, da wa’azi iri-iri, tare da misalai daban-daban, duka domin su wa’azantu su bi hanya mai amfani gare su duniya da lahira, to amma waɗanda zukatansu sun riga sun lalace, wannan bai ƙara musu komai ba sai nesanta daga gaskiya.
Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa wa mushirikai cewa, da a ce akwai wasu abubuwan bauta ba Allah ba, kamar yadda suke riyawa, to da sun nemi hanyar yin galaba da samun nasara a kan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai Al’arshi. To amma su da kansu mushirikan sun amince da cewa, allolinsu da suke bauta wa ba sa iya yin komai da kansu kuma ba sa amfanarwa ba sa cutarwa. To idan haka ne me ya sa suke bauta musu ba Allah ba?
Ma’ana ta biyu da wasu malamai suka faɗa ta wannan ayar shi ne, da a ce akwai wasu ababen bauta tare da Allah, to da su ma sun riƙa neman kusanci ne ga Allah ta hanyar yi masa ɗa’a da bautarsa, don haka su mushirikai mene ne ya sa suke bauta musu ba za su bauta wa Allah kai-tsaye ba?!

Sai kuma ya bayyana cewa, duk wata halitta a sama ko a ƙasa mai bauta ce da tasbihi ga Allah. Sammai bakwai da ƙasa da duk abubuwan da suke cikinsu dukkansu suna tasbihi ne da tsarkake Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Komai ma yana tasbihi ne tare da tsarkake Allah, to amma mutane ba sa fahimtar yadda suke yin tasbihinsu, domin suna yi ne da wani harshe ba irin na mutane ba.

Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Haƙiƙa mun kasance muna jin tasbihin abinci yayin da ake cin sa.” [Bukhari #3579].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yawan haƙurinsa ga masu bijire wa umarninsa da ba ya gaggauto musu da uƙuba, yana kuma gafarta musu yayin da suka tuba suka nemi gafararsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan niyyar bawa ta zamanto ba mai kyau ba yayin sauraron gaskiya to Allah yakan iya hana masa fahimtar gaskiyar.

2. Abul Jauza Ausu ɗan Abdullahi ya ce: “Babu abin da yake korar Shaiɗan daga zuciya kamar faɗin: “*La ilaha illallahu*,” sannan sai ya karanta aya ta 46 a wannan Surar. [Dubi, Al-Kurɗubi, Juzu’i na 10, shafi na 271].

Suratul Isra’i (45-48)
وَإِذَا قَرَأۡتَ ٱلۡقُرۡءَانَ جَعَلۡنَا بَيۡنَكَ وَبَيۡنَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ حِجَابٗا مَّسۡتُورٗا ٤٥ وَجَعَلۡنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ أَكِنَّةً أَن يَفۡقَهُوهُ وَفِيٓ ءَاذَانِهِمۡ وَقۡرٗاۚ وَإِذَا ذَكَرۡتَ رَبَّكَ فِي ٱلۡقُرۡءَانِ وَحۡدَهُۥ وَلَّوۡاْ عَلَىٰٓ أَدۡبَٰرِهِمۡ نُفُورٗا ٤٦ نَّحۡنُ أَعۡلَمُ بِمَا يَسۡتَمِعُونَ بِهِۦٓ إِذۡ يَسۡتَمِعُونَ إِلَيۡكَ وَإِذۡ هُمۡ نَجۡوَىٰٓ إِذۡ يَقُولُ ٱلظَّٰلِمُونَ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا رَجُلٗا مَّسۡحُورًا ٤٧ ٱنظُرۡ كَيۡفَ ضَرَبُواْ لَكَ ٱلۡأَمۡثَالَ فَضَلُّواْ فَلَا يَسۡتَطِيعُونَ سَبِيلٗا ٤٨

45. Idan ka karanta Alƙur’ani Mukan sanya shamaki mai karewa tsakaninka da waɗanda ba sa imani da lahira.

46. Kuma Mukan sanya marufi a kan zukatansu don kada su fahimce shi (Alƙur'anin); a cikin kunnuwansu kuma (Mukan sanya) wani nauyi. Idan kuma ka ambaci Ubangijinka Shi kaɗai a cikin Alƙur'ani sai su ba da baya suna masu bazama.

47. Mu Muka fi kowa sanin irin yadda suke sauraren sa (Alƙur'ani), yayin da suke sauraren ka (kana karanta shi), da kuma sanda suke tattaunawa, yayin da azzalumai suke cewa: "Ai ba wanda kuke bi face wani sihirtaccen mutum."

48. Duba ka ga yadda suka yi ta ba ka sifofi (iri-iri), sai suka ɓace, ba ko za su sami damar (gane) hanya ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin kafirai lokacin da suke sauraron karatun Alƙur'ani daga Manzon Allah (ﷺ). Watau idan suka ji abin da ya ƙunsa na wa'azuzzuka da tsawatarwa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya wani shamaki tsakaninsa da waɗanda ba su yi imani da ranar lahira ba ya hana su fahimtar haƙiƙanin abin da ake karanta musu, don haka sai su bijire masa, su ƙi miƙa wuya gare shi.
Sannan kuma Allah ya saka wasu murafa a kan zukatansu, don haka sai su kasa fahimtar ayoyin Alƙur'ani, ya kuma toshe kunnuwansu da wani nauyi, don haka ba za su taɓa yin sauraro na amfana ba sai dai na tsayuwar hujja a kansu. Don haka ne ma duk sanda Annabi (ﷺ) ya karanta ayoyin Alƙur'ani masu nuna Kaɗaitakar Allah da hana shirka sai su juya baya a guje suna masu watsi da ayoyinsa da suka ji.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin da ya sa ya hana musu fahimtar Alƙur'ani yayin da ake karanta musu shi, da cewa, ya fi kowa sanin mummunar manufarsu lokacin da suke sauraron Alƙur'ani, watau suna sauraro ne da nufin su sami abin da za su kushe shi ne, don haka ba neman gaskiya ne a zukatansu ba, shi ya sa Allah ya toshe musu kafofin fahimtarsa. Haka kuma yana sane da duk abin da suke haɗuwa suna ƙullawa da junansu domin su ƙirƙiri sunan da za su ɓata Manzon Allah (ﷺ) da shi. Azzalumai kuma waɗanda suka cuci kawunansu da kafirci sun fito ƙarara suna faɗa wa mutane cewa, wai idan har suka bi Manzon Allah (ﷺ) to su sani ba wani suke bi ba sai mutumin da aka sihirce shi don haka ya sami taɓin hankali.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Annabinsa cewa, ya duba ya ga yadda kafirai suka bayar da wani gurɓataccen misali marar tushe da dalili, a kansa, inda suka kira shi matsafi, wasu su ce wanda aka sihirce, wasu kuma su ce mawaƙi wasu kuma boka.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, dukkansu sun ɓace ba kuma za su taɓa gane gaskiya ba har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi a kan kusantowar ranar alƙiyama. Duk abin da yake tafe to kusa yake; duk abin da aka tabbatar zai faru to mai faruwa ne komai daɗewa.

2. Ba wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da shi lokacin tashin alƙiyama. Don haka babu wani mala'ika ko wani annabi ko wani salihi da ya san lokacin zuwanta.

3. Duk tsawon ran da mutum zai yi a duniya da shekarun da zai kwashe a ƙabarinsa, wannan ɗan lokaci ne ƙanƙani idan aka kwatanta shi da rayuwar alƙiyama da ta Aljanna da wuta.

Suratul Isra'i (49-52)

وَقَالُوٓاْ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمٗا وَرُفَٰتًا أَءِنَّا لَمَبۡعُوثُونَ خَلۡقٗا جَدِيدٗا ٤٩ ۞قُلۡ كُونُواْ حِجَارَةً أَوۡ حَدِيدًا ٥٠ أَوۡ خَلۡقٗا مِّمَّا يَكۡبُرُ فِي صُدُورِكُمۡۚ فَسَيَقُولُونَ مَن يُعِيدُنَاۖ قُلِ ٱلَّذِي فَطَرَكُمۡ أَوَّلَ مَرَّةٖۚ فَسَيُنۡغِضُونَ إِلَيۡكَ رُءُوسَهُمۡ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هُوَۖ قُلۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَرِيبٗا ٥١ يَوۡمَ يَدۡعُوكُمۡ فَتَسۡتَجِيبُونَ بِحَمۡدِهِۦ وَتَظُنُّونَ إِن لَّبِثۡتُمۡ إِلَّا قَلِيلٗا ٥٢

49. Kuma suka ce: "Yanzu kuwa idan muka zama ƙasusuwa kuma rududdugaggu, anya kuwa za a tashe mu a sabuwar halitta?"

50. Ka ce (da su): "Ku zama dutse ko ƙarfe!

51. "Ko kuma duk wata halitta da ta fi girma a ranku (lalle za a tashe ku)." Sannan za su ce: "To wane ne zai dawo da mu?" Ka ce (da su): "Wanda ya halicce ku tun farko." Sannan za su girgiza maka kawunansu su kuma ce: "To yaushe ne shi (wannan al'amari zai kasance)?" Ka ce (da su): "Mai yiwuwa ne ya faru ba da daɗewa ba.

52. "Ranar da zai kira ku sai ku amsa tare da gode masa kuma ku riƙa tsammanin ba ku zauna (a bayan ƙasa ba) sai ɗan lokaci ƙanƙani."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai suka riƙa ƙaryata tashi bayan mutuwa, har suna mamakin wai ta yaya za a tashe su bayan sun mutu sun zama ƙasusuwa, jikinsu ya ratattake, suka nuna wai wannan abu sam ba mai yiwuwa ne ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya mayar musu da martani cewa, su rikiɗa su zama dutse ko ƙarfe ko duk wani abu da suke ganin babba ne a idonsu, idan suna zaton in sun yi haka Allah ba zai iya dawo da su yadda suke da farko ba. Lalle duk yadda suka zama ba za su gagari Allah ba. Allah zai dawo da su yadda suke da farko. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk da haka za su riƙa tambaya ta izgili suna cewa, wane ne zai dawo da su da ransu bayan sun mutu? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, wannan dai da ya halicce su lokacin da babu su ba tare da ya kwaikwaya daga kowa ba, shi ne dai zai sake dawo da su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, za su riƙa kaɗa kansu suna izgili da amsar da Manzon Allah (ﷺ) ya ba su. Sai su sake masa wata tambayar don dai su ƙure shi, su ce: To yaushe ne za a tashe su? Allah ya umarce shi da ya faɗa musu cewa, tabbas hakan zai faru ba da jimawa ba.
Amma Allah ya bayyana ranar da zai dawo da su gaba ɗayansu, watau ranar da zai kirawo su don su tattaru domin hisabi; nan take kuwa su amsa masa tare da yi masa kirari da miƙa wuya ga umarninsa. A lokacin ne za su yi mamaki su yi tsammanin 'yan kwanaki kaɗan suka yi a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Luɗufin Allah ne ga bayinsa da ya umarce su da bayyana kyawawan halaye da ayyuka da maganganu domin dacewa, da rabon duniya da na lahira.

2. Umarni da kyakkyawar magana ya ƙunshi umarni da duk wata magana da za ta kusanta bawa ga Ubangijinsa kamar karatun Alƙur'ani da ambaton Allah da karatun ilimi da umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna da yi wa mutane magana mai kyau.

3. Idan aka samu abubuwa biyu masu kyau waɗanda ba za a iya haɗa su lokaci ɗaya ba, to sai a zaɓi wanda ya fi kyau daga cikinsu.

4. Maganin Shaiɗan shi ne kauce wa yi masa biyayya wajen furta munanan maganganu, idan mutane suka tausasa magana a tsakaninsu to sun magance sharrin Shaiɗan mai son haddasa husuma a tsakaninsu.

5. Sanin ɗan Aljanna da ɗan wuta na ga Allah shi kaɗai.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fifita wasu annabawa a kan wasu. Manzanni sun fi annabawa. Allah ya fifita biyar daga cikin manzanni a kan sauran, su ne Annabi Nuhu da Annabi Ibrahimu da Annabi Musa da Annabi Isa da Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare su baki ɗaya. Mafi daraja a cikin biyar ɗin nan shi ne Annabi Muhammadu (ﷺ) sai kuma Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Suratul Isra'i (53-55)

وَقُل لِّعِبَادِى يَقُولُواْ ٱلَّتِى هِىَ أَحۡسَنُۚ إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ يَنزَغُ بَيۡنَهُمۡۚ إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ كَانَ لِلۡإِنسَٰنِ عَدُوّٗا مُّبِينٗا ٥٣ رَّبُّكُمۡ أَعۡلَمُ بِكُمۡۖ إِن يَشَأۡ يَرۡحَمۡكُمۡ أَوۡ إِن يَشَأۡ يُعَذِّبۡكُمۡۚ وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ عَلَيۡهِمۡ وَكِيلٗا ٥٤ وَرَبُّكَ أَعۡلَمُ بِمَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَلَقَدۡ فَضَّلۡنَا بَعۡضَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ عَلَىٰ بَعۡضٖۖ وَءَاتَيۡنَا دَاوُۥدَ زَبُورٗا ٥٥

53. Ka kuma ce da bayina su faɗi (magana) wadda ita ce ta fi kyau. Lalle Shaiɗan yana ɓata tsakaninsu. Lalle Shaiɗan ya tabbata maƙiyi ne mai bayyana (ƙiyayya) ga mutum.

54. Ubangijinku (Shi) Ya fi sanin ku; in Ya ga dama sai Ya ji ƙan ku ko kuma in Ya ga dama sai Ya azabtar da ku. Ba Mu kuwa aiko ka ba don ka zama wakili a kansu.

55. Ubangijinka kuma (Shi ne) Mafi sanin abin da yake cikin sammai da ƙasa. Haƙiƙa kuma Mun fifita wasu annabawa a kan wasu; Muka kuma bai wa Dawuda (littafin) Zabura.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya gaya wa muminai su riƙa faɗar kyakkyawar magana a lokacin tattaunawarsu da juna, domin Shaiɗan har koyaushe yana ƙoƙarin ɓata tsakaninsu ne, don haka zai iya haddasa husuma da sharri a tsakaninsu ta hanyar maganar da za su furta wa juna idan ba ta kasance mai kyau ba. Domin shi Shaiɗan maƙiyi ne ga Annabi Adamu da zurriyarsa tun lokacin da ya ƙi yin sujjada ga Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuma ƙiyayyarsa a fili take ba a ɓoye ba.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kada ɗayanku ya nuna ɗan'uwansa da makami domin bai sani ba mai yiwuwa ne Shaiɗan ya kwaɓi hannunsa sai ya jawo masa faɗawa ramin wuta." [Bukhari #7072 da Muslim #2617].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutane cewa, ya fi su sanin kawunansu, domin babu abin da zai ɓoyu gare shi; ya san wanda ya cancanci shiriya daga cikinsu sai ya ji ƙan sa ya shirye shi idan ya ga dama, ya san kuma wanda bai cancance ta ba sai ya bar shi cikin ɓata don ya yi masa azaba idan ya ga dama. Ya tabbatar wa da Annabi (ﷺ) cewa, bai aiko shi don ya zamanto wakili mai tursasa kafirai sai sun yi imani ko mai ƙididdige ayyukansu ba. Shi kawai mai gargaɗi ne da yin albishir ga mutane.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake sanar da mutane cewa, ya fi kowa sanin halittunsa na sama da na ƙasa, ya kuma san matsayin kowa a wajen ayyukan ƙwarai da waɗanda ba na ƙwarai ba. Kuma shi ne ya

fifita wasu annabawa a kan wasu da yawan mabiya da saukar musu da littattafai; shi ne kuma ya ba wa Annabi Dawuda littafin Zabura.

An karƀo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “An sassauta wa Dawuda abin karantawarsa (Zabura); yakan yi umarni a ɗaura wa dabbarsa sirdi, yakan sauke littafinsa kafin a gama sa wa dabbar sirdin.” [Bukhari #4713].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu mai iya hana aukuwar cuta ko yaye ta idan ta auku sai Allah kaɗai.

2. Dukkan salihan bayin Allah suna neman kusanci ne da Allah ta hanyar yi masa ɗa’a da guje wa haninsa.

3. Tsoron Allah da fatan samun rahamarsa da soyayyarsa, waɗannan siffofi ne da Allah ya siffanta mutanen ƙwarai da su. Duk wanda ya siffantu da su kuwa to ya gama samun duk wani alheri daga Allah. Wanda kuwa ya rasa ɗaya daga cikinsu to ya gama taƀewa duniya da lahira.

4. Zunubbai su ne musabbabin duk wata uƙuba da za ta auka wa ƙasa ko al’umma.

Suratul Isra’i (56-58)

قُلِ ٱدۡعُواْ ٱلَّذِينَ زَعَمۡتُم مِّن دُونِهِۦ فَلَا يَمۡلِكُونَ كَشۡفَ ٱلضُّرِّ عَنكُمۡ وَلَا تَحۡوِيلًا ٥٦ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ يَبۡتَغُونَ إِلَىٰ رَبِّهِمُ ٱلۡوَسِيلَةَ أَيُّهُمۡ أَقۡرَبُ وَيَرۡجُونَ رَحۡمَتَهُۥ وَيَخَافُونَ عَذَابَهُۥٓۚ إِنَّ عَذَابَ رَبِّكَ كَانَ مَحۡذُورٗا ٥٧ وَإِن مِّن قَرۡيَةٍ إِلَّا نَحۡنُ مُهۡلِكُوهَا قَبۡلَ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ أَوۡ مُعَذِّبُوهَا عَذَابٗا شَدِيدٗاۚ كَانَ ذَٰلِكَ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مَسۡطُورٗا ٥٨

56. Ka ce (da su): “Ku kirawo waɗanda kuka riya (cewa su ne iyayen gijinku) ba Shi ba, to ba su da ikon yaye muku cuta ko juyar da ita.”

57. Waɗancan da suke bauta wa, su ma suna neman hanya ne zuwa ga Ubangijinsu, a cikinsu wa zai fi kusanci? Suna kuma ƙaunar rahamarsa, kuma suna tsoron azabarsa. Lalle azabar Ubangijinka ta kasance abar tsoro ce.

58. Kuma ba wata alƙarya sai Mu ne masu halaka ta tun kafin ranar alƙiyama, ko kuma Masu azabtar da ita azaba mai tsanani. Wannan ya tabbata a rubuce cikin Littafi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba mu labarin wasu aljannu ne da wasu mushirikai suke bauta musu, sai suka musulunta, su kuma masu bautar su suka ci gaba da bautar su ba tare da sun san cewa, aljannun nan sun musulunta ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake umartar Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa mushirikai cewa, su kirawo waɗanda suke bauta wa ba Allah ba, ba za su iya kare su daga wata cuta da za ta same su ba, ba kuma za su iya ɗauke musu ita ba su jefa wa wani domin gajiyawarsu da kasawarsu; duk wani gajiyayye kuwa ba zai taƀa zama abin bauta ba. Sannan ya sanar da su cewa, waɗannan da suke bauta wa daga cikin aljannu da mala’iku da sauran mutanen kirki su kansu suna neman kusanci ne wurin Allah ta hanyar ayyuka na ƙwarai, suna rigegeniya a tsakaninsu wajen yi masa ɗa’a, suna fatan samun rahamarsa suna kuma tsoron azabarsa. Lalle kam azabar Allah abar tsoro ce.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu wata alƙarya da mutanenta suka ƙaryata manzannin Allah sai ya hallaka su ya saukar musu da azaba a nan duniya saboda kafircinsu, ko kuma ya azabtar da su da wata azaba mai tsanani kamar kisa da ɗauri da makamantansu. Wannan hallakarwar wani hukunci ne na Allah da ya riga ya rubuta a cikin littafin Lauhul Mahfuzu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashi ga Annabi (ﷺ) game da kwaɗayinsa da ƙaunarsa na ganin mutanensa sun musulunta, don haka yakan so a ce an amsa buƙatarsu ta saukar da wasu ayoyi domin su gamsu su musulunta.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya keɓance Samudawa da ambato a nan domin al'amarinsu shahararre ne a wurin Larabawa, sannan suna wucewa ta garuruwansu suna ganin kufaifansu inda aka hallaka su, tsakanin Makka da Sham.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙyale Kuraishawa bai hallaka su ba ne saboda wata babbar hikima tasa, watau wanzar da su domin ya san da yawa daga cikinsu za su shiga Musulunci kuma Musulunci zai yaɗu ta hannun da dama daga cikinsu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai bayyana wasu manya-manyan ayoyinsa a fili ba domin gudun kada mutane su gan su su ƙaryata su, saboda ba su saba ganin irinsu ba. Don haka rashin bayyana su wata rahama ce gare su.

Suratul Isra'i (59-60)

وَمَا مَنَعَنَآ أَن نُّرۡسِلَ بِٱلۡأٓيَٰتِ إِلَّآ أَن كَذَّبَ بِهَا ٱلۡأَوَّلُونَۚ وَءَاتَيۡنَا ثَمُودَ ٱلنَّاقَةَ مُبۡصِرَةٗ فَظَلَمُواْ بِهَاۚ وَمَا نُرۡسِلُ بِٱلۡأٓيَٰتِ إِلَّا تَخۡوِيفٗا ٥٩ وَإِذۡ قُلۡنَا لَكَ إِنَّ رَبَّكَ أَحَاطَ بِٱلنَّاسِۚ وَمَا جَعَلۡنَا ٱلرُّءۡيَا ٱلَّتِيٓ أَرَيۡنَٰكَ إِلَّا فِتۡنَةٗ لِّلنَّاسِ وَٱلشَّجَرَةَ ٱلۡمَلۡعُونَةَ فِي ٱلۡقُرۡءَانِۚ وَنُخَوِّفُهُمۡ فَمَا يَزِيدُهُمۡ إِلَّا طُغۡيَٰنٗا كَبِيرٗا ٦٠

59. Kuma ba abin da ya hana Mu aiko da ayoyi sai don (al'ummu) na farko sun ƙaryata su; Muka kuma bai wa Samudawa taguwa (don ta zama aya) bayyananniya, sai suka butulce mata. Ba Ma kuwa aiko da ayoyi sai don tsoratarwa.

60. (Ka tuna) kuma lokacin da Muka ce da kai: "Lalle Ubangijinka Ya kewaye mutane (da ikonsa)." Ba Mu kuwa sanya abin da Muka nuna maka ido-da-ido ba (lokacin Isra'i) sai don jarraba ga mutane, da kuma la'ananniyar bishiyar nan (da aka ambata) a cikin Alƙur'ani. Muna kuwa tsoratar da su ne, amma ba abin da yake ƙara musu sai ɗagawa mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana rahamar da ya yi wa mutane yayin da ya ƙi amsa kiran mushirikai na ya sauko da wasu mu'ujizoji don tabbatar da gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ). Ya nuna cewa, ba abin da ya hana shi sauko da su sai don cewa al(Allah ya ƙara masa yarda) 'ummu na farko sun ƙaryata irinsu; don haka idan yanzu ma ya sauko da wasu mushirikai za su ƙaryata su, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gaggauto musu azaba kamar yadda ya yi wa al(Allah ya ƙara masa yarda) 'ummun farko bayan sun ƙaryata mu'ujizojin annabawansu. Taguwar Annabi Salihu tana daga cikin manya-manyan ayoyin da Allah ya aiko, amma duk da haka Samudawa suka ƙaryata ta, Allah kuwa ya saukar musu da azaba, kamar yadda ya bayyana a wasu wurare na Alƙur'ani. To haka su ma waɗannan mushrikai da zai aiko musu da wasu manya-manyan ayoyinsa to da sun ƙaryata su sun ƙi yin imani.

Domin ba rashin ganin hujja ce ya hana musu yin imani ba; an ba su hujjoji masu yawa amma suka yi watsi da su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yana aiko da ayoyi ne kawai domin tsoratarwa, ba domin tursasawa ba.
Sannan Allah ya tunatar da Annabi (ﷺ) lokacin da ya ce da shi, lalle Kudurarsa ta kewaye mutane gaba ɗaya, dukkansu suna ƙarƙashin ikonsa, don haka shi ne mai kare Annabinsa daga sharrin duk wani masharranci, har sai ya isar da saƙon Allah ba tare da ya ji tsoron kowa ba. Ya kuma tabbatar masa da cewa, abin nan da ya nuna masa a daren Isra'i, ya gan shi da idonsa ya yi haka ne don ya jarraba mutane, saboda wasu za su gaskata shi, wasu kuma su ƙaryata shi. Hakanan labarin la'ananniyar bishiyar nan ta zaƙƙumi da ya bayar a Alƙur'ani da cewa, tana tsirowa daga ƙarƙashin wutar Jahannama, to ita ma wata jarrabar ce a gare su; wasu za su gaskata su yi imani, wasu kuwa su ƙaryata su kafirce, domin suna ganin ba ta yadda za a yi bishiya ta tsiro a tsakiyar wuta. To idan ba su yi imani da waɗannan ayoyi biyu ba, ba za su taɓa yin imani da wasu ayoyin ba ko da an saukar musu su.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yana tsoratar da su da ayoyi amma babu abin da tsoratarwar take ƙara musu sai zakewa a kan kafirci da dogewa a cikin ɓata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karrama ɗan'adam tun farkon halittarsa.

2. Shaiɗan tsohon maƙiyin ɗan'adam ne tun lokacin da Allah ya fara halittar mutum na farko.

3. Duk wani sauti mai kira zuwa ga saɓon Allah da duk wani mahayin abin hawa ko mai tafiya da ƙafa cikin saɓon Allah to sun shiga cikin hanyoyin Shaiɗan da rundunarsa.

4. Duk wani saɓon Allah da ke da alaƙa da dukiya, kamar hana zakka ko neman dukiya ta hanyar haramun, kamar cin riba da saye da sayarwa na haramun da cin rashawa da cin dukiyoyin mutane ba bisa haƙƙi ba, duk sun shiga cikin tarayyar Shaiɗan cikin dukiyar mutane.

5. Duk wani sakaci wajen tarbiyyar yara da sa musu sunayen da suka saɓa wa shari'a da haihuwarsu ba a inuwar aure ba, duk waɗannan suna cikin tarayyar Shaiɗan a 'ya'yan mutane.

6. Duk masu dogaro da Allah cikin lamurransu to Shaiɗan ba ya da wani iko a kansu.

Suratul Isra'i (61-65)
وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا۟ لِءَادَمَ فَسَجَدُوٓا۟ إِلَّآ إِبْلِيسَ قَالَ ءَأَسْجُدُ لِمَنْ خَلَقْتَ طِينًا ﴿٦١﴾ قَالَ أَرَءَيْتَكَ هَٰذَا ٱلَّذِى كَرَّمْتَ عَلَىَّ لَئِنْ أَخَّرْتَنِ
إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ لَأَحْتَنِكَنَّ ذُرِّيَّتَهُۥٓ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٦٢﴾ قَالَ ٱذْهَبْ فَمَن تَبِعَكَ مِنْهُمْ فَإِنَّ جَهَنَّمَ جَزَآؤُكُمْ جَزَآءً مَّوْفُورًا ﴿٦٣﴾ وَٱسْتَفْزِزْ مَنِ
ٱسْتَطَعْتَ مِنْهُم بِصَوْتِكَ وَأَجْلِبْ عَلَيْهِم بِخَيْلِكَ وَرَجِلِكَ وَشَارِكْهُمْ فِى ٱلْأَمْوَٰلِ وَٱلْأَوْلَٰدِ وَعِدْهُمْ ۚ وَمَا يَعِدُهُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ إِلَّا غُرُورًا ﴿٦٤﴾ إِنَّ
عِبَادِى لَيْسَ لَكَ عَلَيْهِمْ سُلْطَٰنٌ ۚ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ وَكِيلًا ﴿٦٥﴾

61. Kuma (ka tuna) lokacin da Muka ce da mala'iku: "Ku yi sujjada ga Adamu." Sai suka yi sujjadar in ban da Iblis da ya ce: "Yanzu na yi sujjada ga wanda Ka halitta da taɓo?"

62. Ya ce: "Ka gan Ka, wannan da Ka fifita shi a kaina, tabbas idan Ka jinkirta min har zuwa ranar alƙiyama to lalle zan karkatar da zuriyarsa, sai dai kaɗan (daga cikinsu)."

63. (Allah) Ya ce: “Je ka (an jinkirta maka ɗin), sai dai (duk) wanda ya bi ka daga cikinsu to lalle Jahannama ce sakamakonku, wanda yake sakamako ne cikakke.

64. “Ka kuma yi wasa da hankalin wanda ka sami dama daga cikinsu da muryarka ka kuma jawo su da rundunarka mahaya da na ƙasa; ka kuma yi tarayya da su cikin dukiyoyi da ‘ya’yaye; ka kuma yi musu alƙawari.” Shaiɗan kuwa ba wani alƙawari da yake yi musu sai na ruɗi.

65. “Lalle bayina ba ka da iko a kansu.” Kuma Ubangijinka Ya isa zama Wakili.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tuna wa Annabi (ﷺ) hassadar Iblisu ga Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da zurriyyarsa tun lokacin da Allah ya halicci Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya umarci mala’iku da su faɗi su yi sujjadar gaisuwa gare shi. Duk kuwa suka faɗi suka yi masa sujjada in ban da Iblis shi kaɗai ya ƙi yin sujjada saboda girman kai da hassada. Ya nuna ba zai taɓa yi wa Adamu sujjada ba saboda wai an halicce shi da taɓo shi kuma an yi halittarsa da wuta, don haka yake ganin ya fi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daraja.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda Iblis ya fito ƙarara ya nuna hassadarsa da ƙiyayyarsa ga Annabi Adamu da zurriyyarsa, ya faɗa wa Allah a fili cewa, lalle wannan da ya karrama shi a kansa har ya umarce shi da yi masa sujjada, tabbas idan Allah ya jinkirta rayuwarsa zuwa tashin alƙiyama tabbas sai ya hallakar da ‘ya’yansa ya sa sun kauce wa hanya madaidaiciya in ban da ‘yan kaɗan waɗanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zaɓe su saboda ikhlasinsu ya tsare su daga sharrinsa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) amshi roƙonsa da cewa, ya je shi da duk waɗanda suka zaɓi su bi shi su bar Allah, wutar Jahannama ce makomarsu, kuma ita ce cikakken sakamakon ayyukansu na saɓon Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Shaiɗan da ya je ya aikata duk abin da zai iya aikatawa wajen ɓatar da mabiyansa a duniya; ya yi wasa da hankalin duk wanda zai iya wasa da hankalinsa da muryarsa mai kira zuwa ga saɓon Allah. Hakanan ya umarce shi da ya tara musu gangaminsa na mayaƙansa barade mahaya dawakai da masu tafiya da ƙafa. Ya kuma umarce shi da ya yi tarayya da su cikin dukiyoyinsu ta hanyar sanya su su yi amfani da su inda ya saɓa wa shari’a, ya kuma yi tarayya da su a cikin ‘ya’yansu ta hanyar samun su ba tare da aure ba, da raɗa musu sunaye na maguzanci. Ya kuma yi ta musu alƙawura na ƙarya. Da man ba abin da Shaiɗan yake yi wa mabiyansa alƙawari da shi sai kawai ruɗi da ƙarairayi.

An karɓo daga Iyadh ɗan Himar ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: “Na halicci bayina a bisa hanya miƙaƙƙiya ɗoɗar sai shaiɗanu suka karkatar da su daga kan addininsu, suka haramta musu abin da na halatta musu.” [Muslim #2865].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Da a ce idan ɗayanku zai sadu da iyalansa zai ce: “Ya Allah ka nesantar da mu daga Shaiɗan ka kuma nesantar da Shaiɗan daga abin da za ka arzuta mu.” Idan aka ƙaddara samun ɗa a tsakaninsu to ba zai cutar da shi ba.” [Bukhari #141 da Muslim #1434].

An karɓo daga Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan mutum ya zo shiga gidansa ya ambaci sunan Allah ko ya zo cin abincinsa ya ambaci sunan Allah, to Shaiɗan zai ce wa ‘yan’uwansa: “Ba ku sami wurin kwana ba, ba ku kuma sami abincin dare ba.” Idan kuwa ya shiga bai ambaci sunan Allah ba sai Shaiɗan ya ce: “Kun sami wurin kwana.” Idan ya zo cin abinci bai ambaci sunan Allah ba sai ya ce: “Kun sami wurin kwana da abincin dare.” [Muslim #2018].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Shaiɗan cewa, ba shi da wani iko na hallaka bayinsa na ƙwarai; shi ne zai kare su daga sharrinsa kuma ya ishe su abin dogaro.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samuwar abubuwan sufuri na ruwa da na tudu da na sama wata rahama ce ta Allah ga bayinsa; wajibi ne su gode masa a kan haka, su bi umarninsa su guji haninsa.

2. Halaccin tafiye-tafiye a cikin jiragen ruwa domin kasuwanci ko jihadi ko neman ilimi.

3. Mushirikan farko sukan yi watsi da shirkarsu yayin da suka shiga wata masifa, kuma sukan koma ga yin shirka ne yayin da suke cikin walwala da kwanciyar hankali.

4. Duk wanda ya shiga wata matsuwa ya tsantsanta addu'arsa ga Allah, to Allah yana amsa masa addu'arsa ko da kuwa shi kafiri ne.

5. Babban butulci ne na ɗan'adam lokacin da yake cikin wata musiba ya tuna Allah ya roƙe shi don ya yaye masa, amma idan yana cikin walwala sai ya manta da Allah ko ya yi ta saɓa masa.

6. Wajibi ne ga mumini a koyaushe ya zama mai tsoron azabar Allah, domin shi mai iya hallaka shi ne ta inda ya ga dama, ba zai gagare shi ba, kuma babu mai iya kuɓutar da shi.

Suratul Isra'i (66-69)

رَّبُّكُمُ ٱلَّذِى يُزۡجِى لَكُمُ ٱلۡفُلۡكَ فِى ٱلۡبَحۡرِ لِتَبۡتَغُواْ مِن فَضۡلِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ كَانَ بِكُمۡ رَحِيمًا ٦٦ وَإِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فِى ٱلۡبَحۡرِ ضَلَّ مَن تَدۡعُونَ إِلَّآ إِيَّاهُۖ فَلَمَّا نَجَّىٰكُمۡ إِلَى ٱلۡبَرِّ أَعۡرَضۡتُمۡۚ وَكَانَ ٱلۡإِنسَٰنُ كَفُورًا ٦٧ أَفَأَمِنتُمۡ أَن يَخۡسِفَ بِكُمۡ جَانِبَ ٱلۡبَرِّ أَوۡ يُرۡسِلَ عَلَيۡكُمۡ حَاصِبٗا ثُمَّ لَا تَجِدُواْ لَكُمۡ وَكِيلًا ٦٨ أَمۡ أَمِنتُمۡ أَن يُعِيدَكُمۡ فِيهِ تَارَةً أُخۡرَىٰ فَيُرۡسِلَ عَلَيۡكُمۡ قَاصِفٗا مِّنَ ٱلرِّيحِ فَيُغۡرِقَكُم بِمَا كَفَرۡتُمۡ ثُمَّ لَا تَجِدُواْ لَكُمۡ عَلَيۡنَا بِهِۦ تَبِيعًا ٦٩

66. Ubangijinku Shi ne wanda Yake tafiyar da jirgi a kan kogi don ku nemi falalarsa. Lalle Shi Ya kasance Mai rahama ne a gare ku.

67. Idan kuma bala'i ya same ku a cikin kogi sai duk waɗanda kuke kira su ɓace (muku) sai Shi kawai; sannan lokacin da Ya tserar da ku zuwa sarari sai kuka bijire. Kai mutum ya tabbata butulu!

68. Yanzu kun amince da cewa (Allah) ba zai rufto muku da wani ɓangare na tudu ba, ko kuma Ya aiko muku da jifa ta manya-manyan tsakuwoyi, sannan ba za ku sami wani mai tsaro ba?

69. Ko kuma kun amince cewa ba zai mai da ku cikinsa ba (kogin) a karo na biyu, sai Ya aiko muku da ƙaƙƙarfar iska, sai Ya nutsar da ku saboda kafircewar da kuka yi, sannan kuma ba za ku sami wani mai nema muku haƙƙinku ba a wajenmu saboda (halakarwar da Muka yi muku)?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana rahamar da ya yi wa bayinsa ta hanyar hore musu jiragen ruwa manya da ƙanana da kwale-kwale, ya kimsa musu ilimin ƙera su, ya kuma hore musu kogi wanda za su riƙa tafiya a kansa don su sami sauƙin tafiye-tafiyensu da safarar kayayyakin

kasuwancinsu daga gari zuwa gari; daga ƙasa zuwa ƙasa. Wannan ba ƙaramar rahama ya yi wa bayinsa ba, domin shi mai yawan rahama ne gare su a koyaushe.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata rahamar tasa mai nuna Ɗayantakarsa wajen bauta, shi ne idan kafirai suka shiga ruwa suka ga wata halaka ta taso musu gadan-gadan sai su manta da duk wani abin bauta ba Allah ba, su koma suna kiran Allah shi kaɗai suna tsantsanta addu'a gare shi, kai ka ce da man can haka suke yi a rayuwarsu, don sun tabbatar allolinsu ba za su iya tsinana musu komai ba a lokacin. To idan Allah ya yaye musu damuwarsu ya tserar da su zuwa tudu sai su bijire masa, su koma ga halinsu na shirka da Allah da butulce wa ni'imominsa. Allah ya tabbatar da cewa, lalle ɗan'adam ya tabbata butulu ne.
Sai kuma ya tunatar da su wani iko nasa da suke mantawa da shi lokacin da suka butulce masa bayan ya tserar da su, da cewa, yanzu ba sa jin tsoron Allah zai iya kifar da wani ɓangare na tudu da su, ko kuma ya aiko musu wasu manyan tsakwankwani daga sama su yi ta jifan su har su hallaka gaba ɗaya? To me ya sa suke zaton sai a ruwa ne kaɗai Allah zai iya hallaka su, don haka suke tsantsanta addu'a a gare shi a yayin da suke cikin ruwa? Me ya sa ba sa tunanin cewa yana da ikon ya hallaka su ta aiko musu azabarsa ta ƙarƙashin ƙasa ko ta sama ya hallaka su idan ya ga dama?
Sannan Allah ya nuna musu cewa, idan ma suna zaton sai a ruwa ne kaɗai zai iya hallaka su, to ba sa tunanin cewa wata rana zai iya mayar da su cikin kogin a karo na biyu sai kuma ya aiko musu da wata iska mai tsananin gaske wadda za ta riƙa karya duk wani abu da ta biyo ta kansa, sai ya nutsar da su cikin ruwa da wannan iskar saboda butulcinsu da kafircinsu ba tare da sun sami wani mai tsaya musu ba don ya ƙwato su daga hallaka?

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɗan'adam halitta ce mai daraja a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Yana daga cikin girmamawa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan'adam da ya yi shi halitta ce mai son tsafta ta jiki da tufafi da ta muhalli. Ya kuma girmama shi ya halicce shi a miƙe yana tafiya da ƙafafu biyu, yana ci da hannunsa, ya kuma sanya masa ji da gani da hankali da yake iya bambance abubuwa masu amfani da marasa amfani da shi.

Suratul Isra'i (70)

*وَلَقَدۡ كَرَّمۡنَا بَنِيٓ ءَادَمَ وَحَمَلۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِ وَرَزَقۡنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَفَضَّلۡنَٰهُمۡ عَلَىٰ كَثِيرٖ مِّمَّنۡ خَلَقۡنَا تَفۡضِيلٗا ٧٠

70. Haƙiƙa Mun girmama 'yan'dam, Muka kuma ɗauke su (kan ababen hawa) na sarari da na ruwa, Muka kuma arzuta su daga tsarkakan (abubuwa) kuma Muka fifita su a kan wasu da yawa daga abin da Muka halitta nesa ba kusa ba.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falala da girmamawar da ya yi wa 'yan'adam; ya yi musu kyakkyawar halitta, ya ba su hankali da ilimi, ya ma umarci mala'iku su yi wa ubansu Annabi Adamu sujjadar ban girma. Haka kuma ya hore musu ababen hawa na tudu, kamar dawakai da raƙuma da alfadarai da jakuna, da na ruwa, kamar jiragen ruwa manya da ƙanana. Ya kuma arzuta su da daɗaɗan abubuwan ci da na sha. Bugu da ƙari kuma Allah ya fifita 'yan'adam a kan sauran halittunsa da dama. Don haka ya wajaba su gode masa bisa ga waɗannan ni'imomi masu yawa da ya yi musu, su guji yi masa butulci da saɓa masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kowace al'umma a lahira za a bincike ta shin ta yi aiki da shari'ar da Allah ya aiko mata annabinta da shi? Shin ta bi addininsa? Babu wata al'umma da za a yi mata tambaya a kan addinin da ba a umarce ta da bin shari'arsa ba.

2. Babu wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai yi wa azaba sai bayan hujja ta tabbata a kansa.

3. Mutanen ƙwarai Allah zai ba su littafinsu a hannayensu na dama, su tafi suna karanta shi cikin murna da farin ciki domin kyakkyawan sakamako da suka gani. Mutanen banza kuwa za a ba su littafinsu a hannayensu na hagu, baƙin ciki da tashin hankali ya hana su karanta abin da ya ƙunsa na mummunan sakamako gare su.

Suratul Isra'i (71-72)

يَوْمَ نَدْعُواْ كُلَّ أُنَاسٍۭ بِإِمَٰمِهِمْۖ فَمَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ يَقْرَءُونَ كِتَٰبَهُمْ وَلَا يُظْلَمُونَ فَتِيلًا ﴿٧١﴾ وَمَن كَانَ فِي هَٰذِهِۦٓ أَعْمَىٰ فَهُوَ فِي ٱلْأٓخِرَةِ أَعْمَىٰ وَأَضَلُّ سَبِيلًا ﴿٧٢﴾

71. Ranar da za Mu kirawo kowanne (jinsin) mutane da shugabansu, sannan wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na dama to waɗannan za su karanta littafinsu, sannan ba za a zalunce su ko da gwargwadon zaren ƙwallon dabino ne ba.

72. To wanda kuwa ya zamanto makaho a wannan (duniya), to shi a lahira ma makaho ne kuma mafi ɓacewa daga hanyar (gaskiya).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin ranar alƙiyama ranar da zai kirawo kowace al'umma da shugabanta wanda shi ne abin koyinsu a duniya.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "A ranar alƙiyama mai shela zai yi shela ya ce, kowace al'umma ta bi abin da take bauta wa, sai duk masu bautar wanin Allah (kamar gumaka), su yi ta faɗawa cikin wuta, sai ya zamanto babu waɗanda za su rage sai masu bautar Allah shi kaɗai na kirkinsu da wanda ma ba na kirki ba tare da ɓirɓishin Ahlul Kitabi…." [Bukhari #4581 da Muslim #182].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda aka ba su littafinsu a hannunsu na dama, to za su karanta shi cikin farin ciki da murna, a ba su ladansu cikakke, ba za a tauye musu komai daga sakamakon ayyukansu ba, daidai da zaren cikin ƙwallon dabino. To amma wanda yake mai makantar zuciya ne a nan duniya ya kasa ganin gaskiya ya miƙa wuya, to shi kam a ranar alƙiyama ya fi tsananin makanta, ba zai taɓa gane hanyar shiga Aljanna ba, kamar yadda a duniya yake kasa gane hanyar shiriya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk al'ummar da ta ƙaryata manzonta ta kore shi daga ƙasarsa, to Allah zai gaggauto mata da azabarsa.

2. Tsananin buƙatar bawa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da shi a kan gaskiya.

3. Tunatarwa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi (ﷺ) game da ni'imar da ya yi masa na kare shi da ya yi daga sharrin kafirai tana nuna cewa, wajibi ne ga bawa a kullum ya riƙa tunawa da ni'imar da Allah ya yi masa ta kare shi daga faɗawa cikin wata fitina da take kewaye da shi ta ko'ina.

4. Gwargwadon girman matsayin bawa a wurin Allah da yawan ni'imomin da ya yi masa, gwargwadon haka ne zunubinsa shi ma yake girmama yayin da zai aikata laifi.

5. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi nufin hallakar da wata al'umma sai zunubbansu su ƙaru su yi girma, daga nan Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar musu da azabarsa.

Suratul Isra'i (73-77)

وَإِن كَادُواْ لَيَفۡتِنُونَكَ عَنِ ٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ لِتَفۡتَرِيَ عَلَيۡنَا غَيۡرَهُۥۖ وَإِذٗا لَّٱتَّخَذُوكَ خَلِيلٗا ٧٣ وَلَوۡلَآ أَن ثَبَّتۡنَٰكَ لَقَدۡ كِدتَّ تَرۡكَنُ إِلَيۡهِمۡ شَيۡـٔٗا قَلِيلًا ٧٤ إِذٗا لَّأَذَقۡنَٰكَ ضِعۡفَ ٱلۡحَيَوٰةِ وَضِعۡفَ ٱلۡمَمَاتِ ثُمَّ لَا تَجِدُ لَكَ عَلَيۡنَا نَصِيرٗا ٧٥ وَإِن كَادُواْ لَيَسۡتَفِزُّونَكَ مِنَ ٱلۡأَرۡضِ لِيُخۡرِجُوكَ مِنۡهَا وَإِذٗا لَّا يَلۡبَثُونَ خِلَٰفَكَ إِلَّا قَلِيلٗا ٧٦ سُنَّةَ مَن قَدۡ أَرۡسَلۡنَا قَبۡلَكَ مِن رُّسُلِنَاۖ وَلَا تَجِدُ لِسُنَّتِنَا تَحۡوِيلٗا ٧٧

73. Ba shakka kuwa sun kusa su fitine ka game da abin da Muka yi maka wahayinsa don ka ƙaga mana waninsa; da kuwa haka ta faru, to da lalle sun ɗauke ka masoyi.

74. Ba don kuwa Mun tabbatar da kai (a kan umarninmu) ba, haƙiƙa da saura ƙiris ka ɗan karkata gare su.

75. To da lalle kuwa Mun ɗanɗana maka ninkin (azabar) rayuwa da kuma ninkin (azabar) mutuwa, sannan ba za ka samu wani mai taimakon ka a kanmu ba.

76. Ba shakka sun kusa su tunzura ka daga ƙasar (ta Makka) don su fitar da kai daga cikinta; da kuwa sun aikata haka to da ba za su zauna (a cikinta) ba bayanka sai ɗan lokaci ƙanƙani.

77. (Wannan ita ce) irin al'adar waɗanda Muka aiko gabaninka daga manzanninmu; ba kuwa za ka sami canji a al'adarmu ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin kariya da kiyayewa da ya bai wa Annabi (ﷺ) lokacin da kafirai suke ta ƙoƙarin su karkatar da shi daga miƙaƙƙiyar hanya. Har su kafirai sun yi kusa su fitini Annabi (ﷺ) su karkatar da shi daga abin da Allah ya saukar masa na Alƙur'ani don ya ƙirƙiri wata magana wadda ta dace da son zuciyarsu ya jingina wa Allah. To Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna masa cewa, da a ce ya amince ya yi maganar da kafiran suke buƙata su ji daga bakinsa, to da lalle sun ɗauke shi babban masoyi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa, duk da haka ba don ya tabbatar masa da zuciyarsa ya cire masa tsananin kwaɗayin musuluntarsu ba, da ya ɗan karkata gare su ya biya musu wasu daga cikin buƙatunsu saboda tsananin yaudararsu da matuƙar kwaɗayinsa ga musuluntarsu. Allah ya tabbatar masa cewa, da ya kuskura ya yi hakan kuwa to da lalle ya ɗanɗana masa ninkin azaba a duniya, ya kuma yi masa ninkin azaba a lahira, sannan ba zai sami wani mai taimakonsa ba da zai kare shi daga azabar Allah. To amma Allah ya tsare shi ya tabbatar da zuciyarsa a kan gaskiya bai saurari buƙatarsu ya biya musu ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafiran Makka suka yi ta tunzura Annabi (ﷺ) suna damun sa da cutarwa iri-iri domin su ga sun kore shi daga garin Makka. Allah ya tabbatar musu

cewa, da sun kuskura sun kore shi daga wannan gari, to da su ma tasu ta ƙare, domin bayan sun fitar da shi to ba za su daɗe ba sai ɗan lokaci ƙanƙani, Allah zai aiko musu da azabarsa ta hallaka su. To amma ba su iya korar sa daga Makka ba har zuwa lokacin da Allah ya yi masa izinin ya fita ya yi hijira zuwa Madina. Wasu malaman tafsiri sun ce, kafiran Makka sun fitar da Annabi (ﷺ) daga garin Makka, don haka Allah ya nuna musu abin da ya tsoratar da su da shi na azaba, domin bayan hijirarsa zuwa Madina ba su wuce shekara ɗaya da rabi ba Allah ya kawo yaƙin Badar, suka fita yaƙi aka kashe manya-manyansu a can. Watau dai Allah ya nuna musu ƙarshensu kamar yadda ya yi musu alƙawari.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, wannan ita ce al'adarsa ga manzannin da ya aiko gabanin Annabi (ﷺ). Duk sanda mutanen kowane manzo suka ƙaryata shi suka kore shi daga ƙasarsa, to Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu azabarsa ta hallaka su baki ɗaya. Wannan sunnar Allah ce da ba ta canjawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A aya ta 78 Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci lokutan sallolin farilla guda biyar a dunƙule. Sunnar Annabi (ﷺ) kuma ta yi bayaninsu daki-daki.

2. Shigar lokaci sharaɗi ne na ingancin salla, kuma sababi ne na wajabtarta; domin Allah ya yi umarni da tsayar da ita a cikin waɗannan lokutan da aka ambata.

3. Sallar azahar da ta la'asar sukan haɗu lokaci ɗaya ga mai uzuri. Hakanan ma sallar magariba da ta isha su ma sukan haɗu ga mai uzuri, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne ya haɗe lokutansu wuri guda.

4. Falalar sallar asuba da falalar tsawaita karatu a cikinta.

5. Mafi ɗaukakar yanayi da Allah zai sanya bawansa a ciki shi ne ya zamanto a cikin kowane hali da yanayi yana tattare da ɗa'ar Allah da bautarsa don neman kusancinsa.

6. Wani lokaci ƙarya takan kasance ta yi ƙarfi, ta yi ta cin karenta babu babbaka, yayin da babu wata gaskiyar da take ƙalubalantar ta. To amma da zarar gaskiya ta bayyana, to nan da nan ƙarya take ja da baya. Wannan ya sa ƙarya take saurin yaɗuwa a wurare da lokutan da babu ilimi na gaskiya a cikinsu.

Suratul Isra'i (78-81)

أَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِدُلُوكِ ٱلشَّمۡسِ إِلَىٰ غَسَقِ ٱلَّيۡلِ وَقُرۡءَانَ ٱلۡفَجۡرِۖ إِنَّ قُرۡءَانَ ٱلۡفَجۡرِ كَانَ مَشۡهُودٗا ٧٨ وَمِنَ ٱلَّيۡلِ فَتَهَجَّدۡ بِهِۦ نَافِلَةٗ لَّكَ عَسَىٰٓ أَن يَبۡعَثَكَ رَبُّكَ مَقَامٗا مَّحۡمُودٗا ٧٩ وَقُل رَّبِّ أَدۡخِلۡنِي مُدۡخَلَ صِدۡقٖ وَأَخۡرِجۡنِي مُخۡرَجَ صِدۡقٖ وَٱجۡعَل لِّي مِن لَّدُنكَ سُلۡطَٰنٗا نَّصِيرٗا ٨٠ وَقُلۡ جَآءَ ٱلۡحَقُّ وَزَهَقَ ٱلۡبَٰطِلُۚ إِنَّ ٱلۡبَٰطِلَ كَانَ زَهُوقٗا ٨١

78. Ka tsayar da salla lokacin zawalin rana zuwa duhun dare, da kuma karatun sallar Asuba. Lalle (lokacin) karatun sallar asuba ya kasance lokacin halartar (mala(Allah ya ƙara masa yarda) 'iku).

79. Da daddare kuwa sai ka yi tsayuwar dare da shi (Alƙur'anin) ƙarin (daraja) ne gare ka, tare da ƙaunar Ubangijinka ya tashe ka a matsayin sha-yabo (watau matsayin mai ceto).

80. Kuma ka ce: "Ubangijina Ka shigar da ni mashiga ta gaskiya, kuma Ka fitar da ni mafita ta gaskiya, kuma Ka ba ni wata hujja mai taimakawa daga gare ka."

81. Kuma ka ce: “Gaskiya ta zo, ɓarna kuma ta watse. Lalle da ma can ita ɓarna ai watsattsiya ce.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sanar Annabi (ﷺ) lokutan salloli biyar ne, inda ya umarce shi da ya tsayar da salla lokacin da rana ta yi zawali, watau ta gushe daga tsakiyar samaniya. A nan sallar Azzahar da La’asar sun shiga ke nan. Sannan da lokacin da dare ya lulluɓe da duhunsa; wannan kuma ya ƙunshi sallar Magariba da sallar Isha’i. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci sallar alfijir, watau sallar Asuba.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Mala’ikun dare da mala’ikun rana suna haɗuwa a lokacin sallar asuba.” [Bukhari #4717 da Muslim #649].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da tashi cikin wani yanki na dare ya yi sallar nafila. Wannan nafilar a wurinsa ƙarin daraja ce gare shi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Manzon Allah (ﷺ), wacce salla ce ta fi falala bayan sallar farilla? Sai ya ce: “Sallar dare.” [Muslim #1163].

Yin hakan zai sanya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tashi Annabinsa a ranar alƙiyama a matsayin babban mai ceton mutane wanda na farko da na ƙarshe za su gode kuma su yaba masa.
Ya tabbata a ingantattun hadisai masu yawa cewa, a ranar alƙiyama bayan an tashi halittu gaba ɗayansu domin yi musu hisabi, za a matso da rana dab da kawunansu, gumi ya kai har wajen kunnuwansu, don haka sai su tafi wurin annabawa ɗaya bayan ɗaya suna neman su cece su daga wannan matsanancin hali, su roƙa musu Allah ya gaggauta yi musu hisabi. Za su fara ne daga Annabi Adamu sannan Annabi Nuhu sannan Annabi Ibrahimu sannan Annabi Musa sannan Annabi Isa; kowanne daga cikinsu zai nuna musu abin ya fi ƙarfinsa, ya gabatar da hanzarinsa, har dai inda za su zo ga Annabi Muhammadu (ﷺ), sai ya faɗa musu cewa wannan matsayi nasa ne, sai ya tafi ya yi sujjada a ƙarƙashin Al’arshi ya yi wa Allah yabo da kirari wanda bai taɓa yi masa irinsa ba. Sai a ce masa ya ɗaga kansa ya roƙi kome yake so, za a ba shi, ya nemi ceton da yake so za a yi masa. Ya ɗago kansa ya ce: “Ya Ubangiji, al’ummata, ya Ubangiji, al’ummata.” Daga nan Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi damar shigar da wasu daga cikin al’ummarsa gidan Aljanna.” [Dubi, Bukhari #3340 da Muslim #194]. Wannan shi ne matsayin na sha-yabo da Allah zai ba shi ranar alƙiyama.
Sai kuma ya umarce shi da ya riƙa roƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya shige da ficensa duka su zama ɗa’a ne ga Allah da neman yardarsa. Ya kuma roƙe shi ya ba shi bayyananniyar hujja mai ƙarfi wadda za ta taimaka masa ya ci nasara a kan maƙiyansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya tabbatar wa mushirikai cewa, gaskiya fa ta zo, watau addinin Musulunci, kuma alƙawarin Allah ya tabbata na ba da nasara ga Annabi (ﷺ) da muminai; ƙarya kuma ta watse, watau shirka da kafirci. Lalle tabbas ƙarya kam ba ta da wurin zama sai watsewa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: A lokacin da Annabi (ﷺ) ya shiga Makka (watau ranar Fat(Allah ya ƙara masa yarda) 'hu Makka), ya samu gumaka har ɗari uku da sittin a kafe a jikin Ka’aba, sai ya riƙa bin su ɗaya bayan ɗaya yana zungurin su da sandarsa suna faɗuwa shi kuma ya riƙa karanta wannan ayar: “Gaskiya ta zo, ƙarya kuma ta gushe, lalle da man ƙarya ta tabbata mai gushewa ce;” da kuma faɗar Allah: “Gaskiya ta zo, ƙarya ba za ta iya farar da komai ba kuma ba za ta iya maimaita shi ba.” [*Suratu Saba*’, aya ta 49] [Bukhari #4720 da Muslim #1781].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani ya ƙunshi waraka ga cututtukan da suke ɓata zuciyar ɗan'adam, kamar cutar shirka da kafirci da munafunci da riya da hassada da sauransu. Wannan shi ne babban jigo na manufofin saukar da shi. Hakanan ana karanta shi domin neman kariya daga shaiɗanu da sharrinsu, kamar yadda ake karanta shi don neman waraka daga cututtukan jiki.

2. Alƙur'ani rahama ne, domin ya ƙunshi bayanin hanyoyin da bawa zai bi domin samun rahama ta Ubangiji a duniya da lahira.

3. Bayanin mummunan halin yawancin 'yan'adam na butulce wa Allah idan ya ba su ni'imominsa.

Suratul Isra'i (82-84)

وَنُنَزِّلُ مِنَ ٱلْقُرْءَانِ مَا هُوَ شِفَآءٌ وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ وَلَا يَزِيدُ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا خَسَارًا ﴿٨٢﴾ وَإِذَآ أَنْعَمْنَا عَلَى ٱلْإِنسَٰنِ أَعْرَضَ وَنَا بِجَانِبِهِۦ وَإِذَا مَسَّهُ ٱلشَّرُّ كَانَ يَوسًا ﴿٨٣﴾ قُلْ كُلٌّ يَعْمَلُ عَلَىٰ شَاكِلَتِهِۦ فَرَبُّكُمْ أَعْلَمُ بِمَنْ هُوَ أَهْدَىٰ سَبِيلًا ﴿٨٤﴾

82. Kuma daga Alƙur'ani Muna saukar da abin da yake shi waraka ne da kuma rahama ga muminai; ba kuma zai ƙari azzalumai (da komai) ba sai taɓewa.

83. Kuma idan Muka yi wa mutum ni'ima sai ya bijire ya kuma juya kwiɓinsa; idan kuwa sharri ne ya same shi sai ya zama mai yawan yanke ƙauna.

84. Ka ce: "Kowa ya yi aiki bisa hanyarsa sai dai Ubangijinku (Shi ne) Mafi sanin wanda ya fi shiriya a kan madaidaiciyar hanya."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falala da albarkar da ke cikin littafinsa Alƙur'ani da cewa, ya ƙunshi waraka ga zukata daga cututtuka irin na kafirci da munafunci da jahilci, kuma waraka ne ga jiki idan an yi ruƙuya da shi. Kuma rahama ne ga muminai masu aiki da koyarwarsa, amma su kafirai babu abin da Alƙur'ani yake ƙara musu sai hallaka da taɓewa, domin sauraron sa yana ƙara baƙanta musu rai, yana nisanta su da shi har su ƙaryata shi su bijire masa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wani mummunan hali na ɗan'adam, shi ne idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa wata ni'ima ta lafiya ko dukiya ko 'ya'ya, sai ya bijire masa ya ƙi godiya gare shi ta hanyar yi masa ɗa'a, sai ma ya ƙara nisa da Ubangijinsa yana girman kai. Amma kuma da zarar wata rashin lafiya ta same shi ko talauci sai ya zamanto mai tsananin ɗebe ƙauna daga rahamar Allah.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya bayyana cewa, kowane mutum yana aikinsa ne a kan hanyarsa wadda ta yi daidai da halayensa, watau idan yana cikin mutanen ƙwarai sai aikinsa ya kasance ga Allah kaɗai; idan kuwa yana cikin taɓaɓɓu to babu aikin da ya dace da shi sai na taɓaɓɓu irinsa. Allah kuma ya tabbatar da cewa, shi ne ya fi kowa sanin wanda ya fi zamantowa a kan miƙaƙƙiyar hanyar shiriya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu wanda ya san haƙiƙanin yadda ruhi yake sai Allah kaɗai, don haka bincike a kansa ɓata lokaci ne.

2. Duk yadda ɗan'adam ya kai ga tumbatsa a ilimi to iliminsa ɗan kaɗan ne a wurin Allah.

3. Yana da kyau idan an yi wa mutum tambayar da ba ta kamata ba, to kada ya ba da amsa a kanta, ya nusar da mai tambayar ga abin da ya dace kuma mai amfani gare shi.

4. Mafi girman ni'imar da Allah ya bai wa Annabi (ﷺ) ita ce Alƙur'ani.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, da a ce mutane da aljannu za su haɗu ba za su iya kawo kwatankwacin wannan Alƙur'ani ba. Wannan babban dalili ne ƙarara da ke nuna gaskiyarsa, kuma abin da Allah ya ambata shi ne ya tabbata, domin masu ƙaryata Alƙur'ani suna bin kowace irin hanya da za su tabbatar da ƙaryar ne, amma sun kasa. Ga su dai Allah ya ba su fasahar harshe da hikima, da a ce suna iya kawo kamarsa to da sun kawo. Amma tun da sun kasa, wannan ya nuna sun miƙa wuya sun saduda.

Suratul Isra'i (85-88)

وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلرُّوحِۖ قُلِ ٱلرُّوحُ مِنْ أَمْرِ رَبِّى وَمَآ أُوتِيتُم مِّنَ ٱلْعِلْمِ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٨٥﴾ وَلَئِن شِئْنَا لَنَذْهَبَنَّ بِٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ ثُمَّ لَا تَجِدُ لَكَ بِهِۦ عَلَيْنَا وَكِيلًا ﴿٨٦﴾ إِلَّا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَۚ إِنَّ فَضْلَهُۥ كَانَ عَلَيْكَ كَبِيرًا ﴿٨٧﴾ قُل لَّئِنِ ٱجْتَمَعَتِ ٱلْإِنسُ وَٱلْجِنُّ عَلَىٰٓ أَن يَأْتُوا۟ بِمِثْلِ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ لَا يَأْتُونَ بِمِثْلِهِۦ وَلَوْ كَانَ بَعْضُهُمْ لِبَعْضٍ ظَهِيرًا ﴿٨٨﴾

85. Suna kuma tambayar ka game da ruhi. Ka ce da su: "Shi ruhi yana daga al'amarin Ubangijina, ba abin da aka ba ku na ilimi sai ɗan kaɗan."

86. Kuma tabbas da Mun ga dama lalle da Mun tafiyar da abin da Muka yo maka wahayi, sannan ba za ka sami wani mataimaki ba a kanmu (game) da shi.

87. Sai dai rahama daga Ubangijinka. Lalle falalarsa gare ka ta zamo mai girma ce.

88. Ka ce da su: "Wallahi da mutane da aljannu sun haɗu kan su kawo irin wannan Alƙur'anin, to ba za su zo da irinsa ba, ko da kuwa wasu sun zamanto suna taimaka wa wasu."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana yadda kafirai suka riƙa yi wa Annabi (ﷺ) tambayoyi irin na ƙalubale ba na neman fahimta ba, har ta kai sun tambaye shi mene ne ruhi (watau rai)? Abin da sun san shi ɓoyayyen abu ne wanda babu mai iya siffanta yadda yake. Duk da cewa akwai abubuwa da yawa waɗanda ba su sani ba kuma suna da buƙatar su san su, amma ba su yi tambaya a kansu ba.
Ruwayoyi biyu sun tabbata wajen tantance masu yin irin wannan tambayar.
Ta farko: An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wata rana muna tafiya tare da Manzon Allah (ﷺ) a cikin wata gona a Madina, yana dogarawa da reshen dabino, sai wasu Yahudawa suka zo wucewa, sai wani daga cikinsu ya ce: "Ku yi masa tambaya game da ruhi." Sai wani ya ce: "Me zai sa ku yi masa tambaya?" Sai wani ya ce: "Kada fa ya fuskance ku da abin da ba zai yi muku daɗi ba." Sai suka ce: "Ku yi masa tambaya game da ruhi." Sai suka yi wa Annabi wannan tambayar. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi shiru bai ba su amsa ba." Ibnu Mas'ud ya ce: "Sai na fahimci wahayi ne ake yi masa, sai na tsaya a inda nake. To lokacin da wahayin ya sauko sai Manzon Allah (ﷺ) ya karanta wannan ayar ta 85." [Bukhari #4721 da Muslim #2794].

Wannan ruwayar ta nuna ayar ta sauka ne a Madina.

Ruwaya ta biyu: An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Kuraishawa sun ce wa Yahudawa: “Ku ba mu wani abu da za mu tambayi wannan mutumin?” Sai suka ce musu: “Ku tambaye shi game da ruhi.” Sai suka tambayi Annabi (ﷺ) game da shi, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar. Sai Yahudawa suka ce: “Mu an ba mu ilimi mai yawa, domin an ba mu Attaura, wanda kuwa aka ba shi Attaura ai an ba shi alheri mai yawa.” Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da aya ta 109 a *Suratul Kahafi*.” [Tirmizi #3140 da Ahmad #2309].

Wannan ruwayar tana nuna an saukar da ayar a Makka ne. Yana yiwuwa kuma an saukar da ayar ne sau biyu. [Dubi, *Fathul Bari*, juzu’i na 8,shafi na 401].
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya bayyana musu cewa, babu wanda ya san haƙiƙanin ruhi sai Allah kaɗai, kuma duk irin yawan ilimin da suke ganin suna da shi to ɗan kaɗan ne idan an kwatanta shi da ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Ubayyu ɗan Ka’ab (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa a ƙissar Annabi Musa da Khadhir (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa: “…sai wani tsuntsu ya sauka a kan gefen jirgin ruwansu, sai ya tsattsagi ruwa da bakinsa sau ɗaya ko sau biyu, sai Khadhir ya ce: “Ya Musa, ilimina da iliminka idan an kwatanta shi da ilimin Allah to bai wuce kamar abin da tsuntsun nan ya tsattsaga daga kogin nan ba.” [Bukhari #122].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Alƙur’ani da ya yi wahayinsa ga Annabi (ﷺ) wata rahama ce gare shi da kuma bayin Allah. Shi ne kuma mafi girman ni’ima da ya yi masa, domin falalarsa gare shi mai girma ce. Don haka wanda ya yi masa wannan falalar yana da ikon ya gusar masa da ita, sannan ba zai sami mai dawo masa da ita ba, ko wani wakili da zai nema masa alfarmar a dawo masa da ita daga Allah ba. Amma saboda rahamar Allah gare shi bai gusar masa da ita ba, ya ci gaba da tsare ta. Lalle falalar Allah ga Manzonsa mai girma ce da ya zaɓe shi a matsayin Manzonsa kuma cikamakin annabawansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ƙalubalanci Larabawa, da sauran mutane, har da aljannu duka su kawo kwatankwacin Alƙur’ani idan suna iyawa. Allah ya tabbatar da cewa, da a ce duk mutane da aljannu za su haɗu domin su zo da wani abu kamar Alƙur’ani mai balaga da fasaha da kyan zubi da azanci irin nasa, to ba za su iya kawo kamarsa ba har abada, ko da kuwa sashensu zai taimaki sashe a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafiran Kuraishawa sun ƙalubalanci Annabi (ﷺ) ya ɓuɓɓugo da idanuwan ruwa a ko’ina a garin Makka. Da Allah ya ga dama da ya yi musu hakan, domin wannan abu ne mai sauƙi a wurinsa, to amma ya san cewa, ko da ya yi hakan ba za su yi imani ba, kamar yadda ya bayyana a [*Suratu Yunusa*, aya ta 96-97].

2. Kafiran Kuraishawa sun ƙalubalanci Annabi (ﷺ) da ya rufto musu da rufin sama ya faɗo musu yanki-yanki kamar yadda yake faɗa musu cewa, lokacin tashin alƙiyama sama za ta tsattsage ta ɓaɓɓangaro. To suna son ya gaggauto musu da hakan tun a duniya. Haka mutanen Annabi Shu’aibu suka yi irin wannan gatsalin sai ko Allah ya aiko musu da azabarsa. To amma shi Manzon Allah (ﷺ) Annabin rahama ne kuma Annabin tuba ne wanda Allah ya aiko shi ya zama rahama ga duniya baki ɗaya. Don haka sai ya roƙi a jinkirta musu azaba, wataƙila wasu daga cikinsu su musulunta, ko kuma Allah ya fitar daga tsatson wasunsu waɗanda za su bauta masa shi kaɗai. Kuma haka ne ya faru, domin wasunsu daga ƙarshe sun musulunta, wasu kuma ‘ya’yansu da jikokinsu sun musulunta, kuma musuluncinsu ya yi kyau.

3. Da yawa daga cikin kafirai sun ƙi musulunta ne saboda ganin Annabi mutum ne kamarsu. Allah kuwa cikin rahamarsa da tausayinsa bai taba aiko wa mutane manzanninsa ba sai daga jinsinsu mutane, domin su za su iya tsayawa su saurare su, su kuma fahimci abin da suke faɗa musu, har ma su iya yin koyi da su. Da kuwa a ce mala'iku ya aiko, to da duk waɗannan abubuwan ba za su yiwu ba.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya isa ya zama shaida ga Manzonsa (ﷺ) tare da mu'ujizojin da ya ba shi na ayoyin da ya saukar masa, da kuma nasara da ya ba shi a kan duk abokan gabarsa. Kuma da a ce ƙarya Annabi (ﷺ) ya yi wa Allah, to tabbas da Allah bai ƙyale shi ba, da ya yi masa matsanancin kamu, ya yi masa azaba mai munin gaske, domin ba abin da Allah bai sani ba, kuma babu mai gagarar sa.

Suratul Isra'i (89-96)

وَلَقَدْ صَرَّفْنَا لِلنَّاسِ فِي هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٍ فَأَبَىٰٓ أَكْثَرُ ٱلنَّاسِ إِلَّا كُفُورًا ﴿٨٩﴾ وَقَالُوا۟ لَن نُّؤْمِنَ لَكَ حَتَّىٰ تَفْجُرَ لَنَا مِنَ ٱلْأَرْضِ
يَنۢبُوعًا ﴿٩٠﴾ أَوْ تَكُونَ لَكَ جَنَّةٌ مِّن نَّخِيلٍ وَعِنَبٍ فَتُفَجِّرَ ٱلْأَنْهَٰرَ خِلَٰلَهَا تَفْجِيرًا ﴿٩١﴾ أَوْ تُسْقِطَ ٱلسَّمَآءَ كَمَا زَعَمْتَ عَلَيْنَا كِسَفًا أَوْ تَأْتِىَ
بِٱللَّهِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةِ قَبِيلًا ﴿٩٢﴾ أَوْ يَكُونَ لَكَ بَيْتٌ مِّن زُخْرُفٍ أَوْ تَرْقَىٰ فِى ٱلسَّمَآءِ وَلَن نُّؤْمِنَ لِرُقِيِّكَ حَتَّىٰ تُنَزِّلَ عَلَيْنَا كِتَٰبًا نَّقْرَؤُهُۥ ۗ قُلْ
سُبْحَانَ رَبِّى هَلْ كُنتُ إِلَّا بَشَرًا رَّسُولًا ﴿٩٣﴾ وَمَا مَنَعَ ٱلنَّاسَ أَن يُؤْمِنُوٓا۟ إِذْ جَآءَهُمُ ٱلْهُدَىٰٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓا۟ أَبَعَثَ ٱللَّهُ بَشَرًا رَّسُولًا ﴿٩٤﴾ قُل لَّوْ كَانَ
فِى ٱلْأَرْضِ مَلَٰٓئِكَةٌ يَمْشُونَ مُطْمَئِنِّينَ لَنَزَّلْنَا عَلَيْهِم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ مَلَكًا رَّسُولًا ﴿٩٥﴾ قُلْ كَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًۢا بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ بِعِبَادِهِۦ
خَبِيرًۢا بَصِيرًا ﴿٩٦﴾

89. Kuma haƙiƙa Mun sarrafa wa mutane kowanne irin misali a cikin wannan Alƙur'ani, sai dai yawancin mutane sun ƙi (komai) sai kafircewa.
90. Suka kuma ce: "Ba za mu yi imani da kai ba har sai ka ɓuɓɓugo mana da idon ruwa daga ƙasa.

91. "Ko kuma ya zamana kana da wata gona ta dabinai da inabi, sai kuma ka ɓuɓɓugo da ƙoramu ta tsakiyarta su kwarara sosai.

92. "Ko kuma ka rufto da sama a kanmu, kamar yadda ka riya, ta faɗo yanki-yanki, ko kuma ka zo da Allah da kuma mala'iku (mu gan su) ido-da-ido!

93. "Ko kuma ya zamana kana da wani gida na zinari, ko kuma ka hau sama, ba kuwa za mu amince da hawan naka ba har sai ka saukar mana da wani littafi da za mu karanta shi." Ka ce (da su): "Tsarki ya tabbata ga Ubangijina, ni ba kowa ba ne face mutum Manzo."

94. Kuma babu abin da ya hana kafirai su yi imani lokacin da shiriya ta zo musu, sai cewar da suka yi: "Yanzu Allah ne zai aiko mutum a matsayin manzo?"

95. Ka ce: "Da mala'iku ne suke tafiya a natse a bayan ƙasa, to da lalle Mun aiko musu mala'ika daga sama a matsayin manzo."

96. Ka ce: "Allah Ya isa shaida tsakanina da ku: Lalle Shi ya zamanto Masani ne ga bayinsa, kuma Mai ganin (abin da suke aikatawa) ne."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya sarrafa ayoyin Alƙur'ani ga mutane ta fuskoki daban-daban: Wani lokaci ta hanyar wa'azi; wani lokaci ta hanyar kwaɗaitarwa; wani lokaci kuwa ta hanyar tsoratarwa; wani sa'in ta hanyar ba da misalai da sauran hanyoyin bayani iri-iri da

Alƙur’ani ya zo da su. To amma duk da haka yawancin mutane sun ƙi yin imani sai ƙaryata shi da kafirce masa suke yi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya labarta mana irin yadda kafirai suka riƙa bijiro wa Manzon Allah (ﷺ) da wasu buƙatu na mu’ujizoji iri-iri suna son sai ya nuna musu su kafin su yi imani da shi. Sun buƙaci mu’ujizoji har guda shida ne.
Ta farko: Suka ce ba za su yi imani da shi ba har sai ya ɓuɓbugo musu da ruwa daga ƙasar Makka mai cike da duwatsu, ruwan kuma ya riƙa gudana ba ƙafewa.
Ta biyu: Ko kuma ya mallaki wani gidan gona mai cike da shuke-shuke kuma ya kwararo da ƙorama a cikinsa mai yawan ruwa wadda za ta shayar da shuke-shuken ciki.
Ta uku: Ko ya rufto musu wani yanki na sama kamar yadda yake riyawa cewa, in sun ƙi yin imani azabar Allah za ta same su.
Ta huɗu: Ko kuma ya kawo musu Allah da mala’iku su gan su ido-da-ido su kuma ba da shaidar cewa, abin da ya zo musu da shi gaskiya ne.
Ta biyar: Ko ya mallaki wani ƙanƙararren gida na zinare.
Ta shida: Ko ya tattaka ya hau sama. Suka ce ko da ma ya hau saman ba za su gaskata shi ba har sai ya sauko musu da wani littafi a rubuce daga Allah da za su karanta cewa, shi Manzon Allah ne a cikinsa.
Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya mayar musu da martani cewa, tsarki ya tabbata ga Allah; shi fa ba wani ba ne face mutum kuma Manzo kamar sauran manzannin Allah, ba shi da ikon ya kawo musu abu ɗaya daga cikin abubuwan nan shida da suka nema.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin da ya hana kafirai su yi imani da Allah da Manzonsa su yi aiki da abin da ya aiko shi da shi wanda kuwa bai wuce cewarsu: Yanzu Allah ne zai aiko mutum a matsayin manzonsa!? Watau me ya hana ya aiko musu mala’ika a matsayin manzonsu? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzon Allah ya mayar musu da martani mai sauƙi na cewa, da a ce mala’iku ne suke tafiya a natse a bayan ƙasa kamar yadda mutane suke tafiya, to da tabbas ya aiko musu da manzo mala’ika irin jinsinsu, domin shi ne zai iya fahimtar da su saƙon da aka aiko shi da shi. A nan ba zai zama da hikima ba a ce ya aiko musu da manzo mutum. To haka lamarin yake game da mutane; ashe mutum ne ya dace ya zamo manzo a gare su ba mala’ika ba.
A ƙarshe dai Allah ya sake umartar Annabi (ﷺ) da ya tabbatar wa kafirai cewa, Allah ya isa ya zama shaida tsakaninsa da su don tabbatar da cewa, shi Manzo ne zuwa gare su kuma ya isar musu da saƙon da aka aiko shi da shi, domin Allah mai cikakken sanin halin da bayinsa suke ciki ne kuma yana ganin komai nasu na sarari da na ɓoye.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shiriya da ɓata a hannun Allah suke ba wani ba; yana shiryar da wanda ya ga dama, yana kuma ɓatar da wanda ya ga dama.

2. A ranar alƙiyama Allah zai tashi kafirai a bisa wani mummunan hali, inda za a riƙa jan su a kan fuskokinsu, ba za a bar su su tafi da ƙafafunsu ba. Wannan kuwa ya faru ne saboda yadda a duniya suka zaɓi su tafi a karkace ba bisa ga miƙaƙƙen tafarkin Allah ba. Hakanan za a tashe su ba sa ganin komai, ba sa iya magana, kuma ba sa jin komai, saboda yadda suka kasance a duniya ba sa ganin gaskiya su ɗauke ta, ba sa iya faɗar gaskiya ba kuma sa iya sauraron ta balle su bi ta. Don haka aka yi musu sakayya a lahira da irin ayyukansu na duniya.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci cewa, wutar Jahannama za ta lafa, duk da cewa a wasu ayoyi na Alƙur’ani ya tabbatar da cewa, ba za a sassauta wa kafirai azaba ba. Don haka wasu malaman tafsiri suka bayyana cewa, lafawarta a nan ana nufin ruruwar da take yi ta hanyar babbaka jikkunan kafirai. To idan ta cinye su ƙurmus sai ta lafa Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake mayar musu da

halittarsu sai wutar ta sake ruruwa. Don haka ba asalin wutar ce take lafawa ba, tana lafawa ne daga ruruwa da cin jikkunan kafirai.

. Duk yadda bawa ya kai ga ciyarwa da kyauta yana nan tattare da sifar rowa. Allah ne kaɗai mai cikakkiyar kyauta da bayarwa babu ƙaƙƙautawa.

Suratul Isra'i (97-100)

وَمَن يَهۡدِ ٱللَّهُ فَهُوَ ٱلۡمُهۡتَدِۖ وَمَن يُضۡلِلۡ فَلَن تَجِدَ لَهُمۡ أَوۡلِيَآءَ مِن دُونِهِۦۖ وَنَحۡشُرُهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ عَلَىٰ وُجُوهِهِمۡ عُمۡيٗا وَبُكۡمٗا وَصُمّٗاۖ مَّأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُۖ كُلَّمَا خَبَتۡ زِدۡنَٰهُمۡ سَعِيرٗا ٩٧ ذَٰلِكَ جَزَآؤُهُم بِأَنَّهُمۡ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَقَالُوٓاْ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمٗا وَرُفَٰتًا أَءِنَّا لَمَبۡعُوثُونَ خَلۡقٗا جَدِيدًا ٩٨ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّ ٱللَّهَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ قَادِرٌ عَلَىٰٓ أَن يَخۡلُقَ مِثۡلَهُمۡ وَجَعَلَ لَهُمۡ أَجَلٗا لَّا رَيۡبَ فِيهِ فَأَبَى ٱلظَّٰلِمُونَ إِلَّا كُفُورٗا ٩٩ قُل لَّوۡ أَنتُمۡ تَمۡلِكُونَ خَزَآئِنَ رَحۡمَةِ رَبِّيٓ إِذٗا لَّأَمۡسَكۡتُمۡ خَشۡيَةَ ٱلۡإِنفَاقِۚ وَكَانَ ٱلۡإِنسَٰنُ قَتُورٗا ١٠٠

97. Wanda kuwa Allah Ya shiryar to shi ne shiryayye; wanda kuwa Ya ɓatar to ba za ka sami wani mai taimakon su ba in ban da Shi; za kuma Mu tashe su ranar alƙiyama a kan fuskokinsu suna makafi, kurame, bebaye; makomarsu Jahannama; duk sanda ta lafa sai Mu ƙara musu ƙunarta.

98. Wannan ne sakamakonsu saboda lalle sun kafirce wa ayoyinmu, suka kuma ce: "Yanzu idan muka zama ƙasusuwa kuma rududdugaggu, anya kuwa za a tashe mu a sabuwar halitta?"

99. Yanzu ba sa gani cewa Allah wanda Ya halicci sammai da ƙasa Mai iko ne a kan Ya halicci irinsu? Ya kuma sanya musu wani lokaci wanda ba kokwanto a cikinsa, sai azzalumai suka ƙi (yin imani) sai kafircewa.

100. Ka ce da su: "Idan da ku ne kuka mallaki taskokin rahamar Ubangijina to lalle da kun riƙe su ƙam-ƙam don tsoron ciyarwa. Mutum kuwa ya tabbata mai tsananin rowa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shiriya da ɓata duk suna hannunsa; idan ya ga dama ya shiryar da bawansa, to wannan shi ne shiryayye na gaske. Wanda kuwa ya ɓatar da shi, to ban da shi babu mai iya shiryar da shi kuma babu mai iya jiɓintar al'amarinsa ya taimaka masa ya kare shi daga azabar Allah ranar da zai tattaro su ana jan su a kan fuskokinsu ba sa gani, ba sa iya magana, ba sa ji. Makomarsu a ranar wutar Jahannama ce; duk sanda ta lafa Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara rura ta da su, haka za a yi ta azabtar da su ba ƙaƙƙautawa.
An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya tambayi Annabi (ﷺ) cewa,: "Ya Annabin Allah, ta yaya za a tashi kafiri a kan fuskarsa ranar alƙiyama?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Yanzu ashe wanda ya ba shi damar tafiya a kan ƙafafunsa a duniya ba zai iya tafiyar da shi a kan fuskarsa ba a ranar alƙiyama?" Sai Katadatu mai ruwayar hadisin ya ce: "E, na rantse da Allah zai iya." [Bukhari #4760 da Muslim #2806].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan sakamako da zai yi wa kafirai bai zalunce su ba; zai yi musu shi ne saboda sun kafirce wa ayoyinsa da manzanninsa sun ƙaryata zuwan ranar alƙiyama wanda duk manzanni suka zo da bayaninsa a littattafai da Allah ya saukar suka kuma ba da labarinsa, amma sai kafirai suka nuna Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai iya tayar da matattu ba, har da cewa, yanzu su idan suka mutu suka zama ƙasusuwa suka ratattake, ta yaya za a sake dawo da halittarsu sabuwa? Suka nuna wannan sam ba zai taɓa faruwa ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, ba sa ganin cewa shi ne ya halicci sammai da ƙasa, waɗanda halittarsu ta fi ta mutane girma? To ta yaya kuma za a ce ba zai iya halittar

mutane kamarsu ba? Duk kuwa wanda zai iya halittar babban abu kamar sama da ƙasa, to babu shakka zai iya halittar ƙaramin abu da bai kai shi ba. Kawai dai Allah ya sanya wa faruwar haka wani lokaci ne da babu makawa sai ya faru. To amma duk da waɗannan hujjoji ƙarfafa kuma bayyanannu azzalumai sun ƙi komai sai kafirci saboda zaluncinsu da son zuciya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata mummunar ɗabi'a ta ɗan'adam, watau tsananin rowa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa wa kafirai cewa, da su ne suke riƙe da taskokin rahamar Allah wadda ba ta ƙarewa, da sun riƙe ta ƙam-ƙam sun hana kowa, don tsoron talauci idan suna bayar da ita. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, wannan ɗabi'a ce ta ɗan'adam, watau tsananin rowa. Sai dai mumini shi ne zai bayar saboda kwaɗayin samun lada a wurin Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba kawai samuwar ayoyi ne zai sa mutane su yi imani ba idan Allah bai nufi imaninsu ba; da a ce haka ne kuwa to da duk mutanen Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun yi imani, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi ayoyi har guda tara amma duk da haka Fir'auna da mutanensa sun ƙaryata shi.

2. Fir'auna ya san Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Manzo ne na Allah, kuma abin da ya zo da shi daga Allah ne, amma ya fito ƙarara ya ƙaryata shi. Don haka fahimtar gaskiya kaɗai ba za ta sa mutum ya ba da gaskiya da ita ba sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa gamon katar.

3. Wajabcin komawa a riƙe Allah yayin da azzalumai suke barazana da kurari.

4. Azzalumai ba su da abin yi don ƙalubalantar masu gaskiya sai amfani da ƙarfin mulki ba ƙarfin hujja ba.

Suratul Isra'i (101-104)
وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَىٰ تِسۡعَ ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٖۖ فَسۡـَٔلۡ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ إِذۡ جَآءَهُمۡ فَقَالَ لَهُۥ فِرۡعَوۡنُ إِنِّي لَأَظُنُّكَ يَٰمُوسَىٰ مَسۡحُورٗا ١٠١ قَالَ لَقَدۡ عَلِمۡتَ مَآ أَنزَلَ هَٰٓؤُلَآءِ إِلَّا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ بَصَآئِرَ وَإِنِّي لَأَظُنُّكَ يَٰفِرۡعَوۡنُ مَثۡبُورٗا ١٠٢ فَأَرَادَ أَن يَسۡتَفِزَّهُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ فَأَغۡرَقۡنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ جَمِيعٗا ١٠٣ وَقُلۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِۦ لِبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱسۡكُنُواْ ٱلۡأَرۡضَ فَإِذَا جَآءَ وَعۡدُ ٱلۡأٓخِرَةِ جِئۡنَا بِكُمۡ لَفِيفٗا ١٠٤

101. Kuma haƙiƙa Mun bai wa Musa ayoyi tara bayyanannu; to ka tambayi Banu Isra'ila lokacin da ya zo musu, sai Fir'auna ya ce da shi: "Lalle ni fa ina tsammanin kai Musa sihirtacce ne!"

102. (Musa) ya ce: "Haƙiƙa ka sani ba wanda ya saukar da waɗannan (ayoyin) sai Ubangijin sammai da ƙasa don su zama hujjoji, kuma lalle ina tsammanin kai Fir'auna halakakke ne."

103. Sai ya yi nufin ya girgiza su a ƙasar (ta Masar don ya fitar da su daga ciki), to sai Muka nutsar da shi da duk wanda yake tare da shi gaba ɗaya.

104. Muka kuma ce da Banu Isra'ila: "Ku zauna a ƙasar (ta Falasɗinu), to idan lokacin alƙiyama ya zo za Mu tattaro ku gaba ɗaya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Annabi Muhammadu (ﷺ) ba shi kaɗai ne wanda Allah ya ba wa ayoyi kuma mutanensa suka ƙaryata shi ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ayoyi har tara; kowace aya ta isa ta zama hujja a

kan manzancinsa. Ayoyin su ne: Sanda da farin hannu da tawayar amfanin gona da ruwa mai kwarara da fari da ƙwarƙwata da kwaɗi da kuma jini. To amma duk da haka mutanensa suka ƙaryata shi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da cewa, ya tambayi Yahudawa abin da ya faru lokacin da ya saukar wa kakanninsu da waɗannan ayoyi, amma sai Fir'auna ya ce masa shi fa yana zatonsa wanda aka yi wa sihiri ne. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya mayar masa da martani da cewa, Fir'auna ya tabbatar a ransa cewa, ba wani ne ya saukar da ayoyin nan tara ba sai Ubangijin sammai da ƙasa; ya saukar da su ne domin su zama shaida a kan Kaɗaitakarsa da gaskiyar manzancin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sannan Annabi Musa ya tabbatar wa da Fir'auna cewa, shi halakakke ne hasararre.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Fir'auna ya yi nufin azabtar da Annabi Musa da jama'arsa ya kore su daga ƙasar Masar, amma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka shi tare da sojojinsa gaba ɗaya a cikin ruwa. Sai kuma bayan Allah ya hallaka Fir'auna da rundunarsa, ya umarci Banu Isra'ila cewa, su je su zauna a ƙasar Sham; idan lokacin tashin alƙiyama ya zo zai tara su gaba ɗaya domin yi musu hisabi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani dukkanshi gaskiya ne, kuma tsararre ne tun lokacin da aka saukar da shi da bayan an saukar da shi har zuwa lokacin da Allah zai ɗauke kayansa daga bayan ƙasa.

2. Babban aikin Manzon Allah shi ne albishir ga muminai da Aljanna da gargaɗi ga kafirai da masu saɓon Allah da wutar Jahannama. Don haka shi ba mai tilasta wa kowa ba ne sai ya yi imani, wanda ya ga dama ya yi imani wanda ya ga dama ya kafirce, sakamako ne dai na Allah yana nan yana jiran kowa.

3. Yana daga cikin hikimomin saukar da Alƙur'ani kaɗan-kaɗan ga mutane gwargwadon buƙatarsu, domin ya yi sauƙin karantawa gare su, su kuma sami damar fahimtar sa cikin sauƙi.

. Jahilai ko masu bijire wa gaskiya ba su da wata hujja, don haka bijirewarsu ko jahilcinsu ba zai ragi gaskiya da komai ba. Hujja tana tare da mautanen kirki masu ilimi masu aiki da iliminsu.

5. Falalar yin yin kuka a salla don tsoron Allah.

6. Addu'a ko karatu a salla ya kamata ya zamanto tsaka-tsaki ba tare da ɗaga murya da ƙarfi ba, ba kuma tare da ɓoye ta gaba ɗaya ba.

Suratul Isra'i (105-111)

وَبِٱلۡحَقِّ أَنزَلۡنَٰهُ وَبِٱلۡحَقِّ نَزَلَۗ وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا مُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ١٠٥ وَقُرۡءَانٗا فَرَقۡنَٰهُ لِتَقۡرَأَهُۥ عَلَى ٱلنَّاسِ عَلَىٰ مُكۡثٖ وَنَزَّلۡنَٰهُ تَنزِيلٗا ١٠٦ قُلۡ ءَامِنُواْ بِهِۦٓ أَوۡ لَا تُؤۡمِنُوٓاْۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ مِن قَبۡلِهِۦٓ إِذَا يُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ يَخِرُّونَ لِلۡأَذۡقَانِ سُجَّدٗا ١٠٧ وَيَقُولُونَ سُبۡحَٰنَ رَبِّنَآ إِن كَانَ وَعۡدُ رَبِّنَا لَمَفۡعُولٗا ١٠٨ وَيَخِرُّونَ لِلۡأَذۡقَانِ يَبۡكُونَ وَيَزِيدُهُمۡ خُشُوعٗا ١٠٩ قُلِ ٱدۡعُواْ ٱللَّهَ أَوِ ٱدۡعُواْ ٱلرَّحۡمَٰنَۖ أَيّٗا مَّا تَدۡعُواْ فَلَهُ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰۚ وَلَا تَجۡهَرۡ بِصَلَاتِكَ وَلَا تُخَافِتۡ بِهَا وَٱبۡتَغِ بَيۡنَ ذَٰلِكَ سَبِيلٗا ١١٠ وَقُلِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي لَمۡ يَتَّخِذۡ وَلَدٗا وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ شَرِيكٞ فِي ٱلۡمُلۡكِ وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ وَلِيٞ مِّنَ ٱلذُّلِّۖ وَكَبِّرۡهُ تَكۡبِيرٗا ١١١

105. Kuma da gaskiya Muka saukar da shi (Alƙur'ani), kuma da gaskiya ya sauko. Ba Mu kuma aiko ka ba sai mai yin albishir,0 mai kuma gargaɗi.

106. Kuma Mun saukar da Kur'ani, Mun bayyana shi don ka karanta wa mutane shi a sannu a hankali, Mun kuma saukar da shi daki-daki.

107. Ka ce da su: "Ko ku yi imani da shi ko kada ku yi imani da shi (duk ɗaya ne)." Lalle waɗanda aka bai wa ilimi gabaninsa (Yahudu da Nasara) idan ana karanta musu shi suna faɗuwa da fuskokinsu suna masu sujjada.

108. Suna kuma cewa: "Tsarki ya tabbata ga Ubangijinmu, lalle alƙawarin Ubangijinmu tabbas ya zamanto abin aikatawa ne."

109. Suna kuma faɗuwa da fuskokinsu suna kuka, Yana kuma ƙara musu ƙasƙantar da kai.

110. Ka ce: "Ku kira (sunan) *Allah* ko ku kira (sunan) *Arrahaman*; kowanne kuka kira to shi Yana da sunaye ne mafiya kyau." Kada kuma ka ɗaga muryarka da (karatun) sallarka, kada kuma ka yi shi a ɓoye, ka nemi tsaka-tsakin wannan.

111. Kuma ka ce, "Yabo da godiya sun tabbata ga Allah wanda bai riƙi ɗa ba, kuma ba Shi da wani abokin tarayya a cikin mulki, kuma ba Shi da wani mataimaki don kare masa ƙasƙanci." Kuma ka girmama shi girmamawa ta sosai.

A ayoyin ƙarshe na wannan Sura Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya saukar da Alƙur'ani wanda yake ƙunshe da gaskiya, kuma a bisa gaskiya ya sauka, watau Allah ya tsare shi bai bari wata ɓarna ko rashin gaskiya ya gauraya da shi ba, domin mala'ika Jibrilu ne ya sauko da shi. Sannan Allah ya tabbatar da cewa, ya aiko Annabi ne da wannan Alƙur'anin domin ya zama mai albishir da gidan Aljanna ga masu tsoron Allah, mai gargaɗi da wuta ga kafirai da masu saɓon Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, ya saukar da Alƙur'ani zuwa ga Annabi (ﷺ) kaɗan-kaɗan kuma daki-daki don ya karanta wa mutane hukunce-hukuncensa gwargwadon buƙatarsu, a cikin shekara ashirin da uku.
Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa kafirai cewa, ko su yi imani da Alƙur'ani ko kada su yi imani da shi duka ɗaya ne, domin shi dai Alƙur'ani tabbas gaskiya ne, Allah ya saukar da shi, da ma kuma ya yi nuni game da shi a littattafan da ya saukar a baya, don haka ya bayyana musu cewa, lalle mutanen kirki masu ilimi daga cikin ma'abota littafi waɗanda suke riƙe da littattafansu ba su canja su ba, idan sun ji ana karanta musu Alƙur'ani sukan faɗi ƙasa da fuskokinsu suna sujjada ga Allah, domin godiya gare shi da ya nufe su da riskar zamanin wannan Manzo da aka ba shi Alƙur'ani, watau Annabi Muhammadu (ﷺ).
A sujjadarsu suna tsarkake Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) daga duk wani abu da mushirikai suke siffanta shi da shi wanda bai dace da shi ba. Suna tabbatar da cewa, duk abin da Allah ya yi alƙawari a kansa ta harshen annabawa da manzanni lalle sai ya tabbata. Suna faɗuwa da fuskokinsu suna kuka domin ƙasƙantar da kansu ga Allah da imani da kuma gaskata littafinsa da Manzonsa (ﷺ). Kuma yana ƙara musu ƙasƙantar da kai da miƙa wuya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa mushirikai waɗanda suka ce ba su yarda da sunan Allah (Arrahman) ba cewa, su kira sunansa (Allah) ko su kira sunansa (Arrahman) duk ɗaya ne babu bambanci a tsakaninsu, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da sunaye mafiya kyau, don haka babu wani sunansa wanda bai dace a kira shi da shi ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana Annabi (ﷺ) ya ɗaga muryarsa da ƙarfi lokacin da yake salla yana karanta Alƙur'ani, kada kuma ya ɓoye karatunsa duka ta yadda sahabbansa ba za su iya jin me yake karantawa kwata-kwata ba. Ya umarce shi da yi karatunsa tsakatsaki, bai ɗaga muryarsa da ƙarfi ba, kuma bai ɓoye ta duka ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Wannan ayar ta sauka ga Manzon Allah ne lokacin yana ɓuya shi da sahabbansa a Makka. Ya kasance a lokacin idan yana jan sahabbansa salla sai ya ɗaga muryarsa da ƙarfi wajen karatun Alƙur’ani, idan mushirikai suka jiyo shi sai su zagi Alƙur’anin su zagi wanda aka saukarwa da shi su zagi wanda ya sauko da shi, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar.” [Bukhari #4722 da Muslim #446].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi yabo da kirari ga Allah wanda ba shi da wani ɗa kuma ba shi da wani abokin tarayya, a mulkinsa shi kaɗai ne, bai haifa ba kuma ba a haife shi ba, kuma ba shi da wani kini ko kishiya, don haka shi ba ƙaskantacce ne ba wanda zai buƙaci mataimaki ko wani waziri ko mai ba shi shawara. Shi ne mahaliccin kowa da komai, mai gudanar da komai shi kaɗai yadda ya ga dama ba tare da abokin tarayya ba. Sannan ya umarce shi ya girmama shi iyakar girmamawa ta hanyar yabonsa da siffanta shi da siffofinsa maɗaukaka da tsarkake shi daga abin da kafirai azzalumai suke siffanta shi da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi kansa bisa ga saukar da Alƙur’ani ga bawansa Annabi Muhammadu (ﷺ) domin shi ne mafi girman ni’imar da ya yi wa mutane a wannan duniya, domin da shi ne ya fitar da su daga duffai zuwa ga haske, kuma shi ne sababin samun tsirarsu a duniya da lahira.

2. Kiran Alƙur’ani da sunan (Allah ya ƙara masa yarda) 'Littafi(Allah ya ƙara masa yarda) ' yana ishara zuwa ga yadda zai zamanto daga ƙarshe, watau za a tattara shi wuri guda a matsayin littafi ɗaya bayan a da yana rubuce ne a cikin wasu abubuwan rubutu daban-daban a wajen sahabbai.

3. Alƙur’ani cikakken littafi ne kuma ingantacce, babu wata tawaya ko saɓani a cikinsa. Duk hukunce-hukuncensa adalci ne, labaran cikinsa kuwa duka gaskiya ne.

4. Babbar manufar saukar da Alƙur’ani ita ce don a yi wa’azi da shi ta hanyar albishir da kuma gargaɗi.

5. Duk masu da’awar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da ɗa ba su da wani dalili daga Allah ko na hankali sai dai shaci-faɗi kawai.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jera matakai uku wajen rushe da’awar masu riya cewa yana da ɗa, ya fara da mafi sauƙin muni har ya zuwa mafi tsananin munin.

Na farko, ya bayyana cewa ba su da wani ilimi a kan haka su da iyayensu. Yin magana ba bisa ilimi ba kuwa ba shakka mummunan abu ne.
Na biyu, ya tabbatar musu da cewa wannan magana da suke furtawa ta kai matuƙa ga muni.
Na uku, ya bayyana musu cewa maganarsu ƙarya ce zunzurutunta babu gaskiya ko kaɗan a cikinta.

7. Tsananin tausayin Annabi (ﷺ) ga al’ummarsa, don haka ya riƙa shiga cikin matsananciyar damuwa a kan rashin ba da gaskiyarsu, har sai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tausaya masa.

8. Duk wani mai kira zuwa ga Allah wajibin da yake kansa shi ne ya yi matuƙar ƙoƙarinsa wajen isar da gaskiya ga mutane da yi musu bayanin hanyar ɓata don su nisance ta. Idan sun shiryu to wannan abin faranta rai ne; idan kuwa sun ci gaba da zama cikin ɓatansu to kada ya saka kansa cikin damuwa da ɓacin rai wanda har zai sa shi ya yi rauni, gwiwarsa ta yi sanyi ya kasa ci gaba da aikinsa na da’awa.

9. Allah ya bayyana cewa duk wani ƙyale-ƙyale a bayan ƙasa na kayan ciye-ciye ko na shaye-shaye ko na tufafi ko wuraren zama ko abubuwan hawa da sauransu, duk wannan jarrabawa ce ta duniya domin a tantance waɗanda suka fi kyautata ayyukansu ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

18-Suratul Kahf

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta ***'Suratul Kahf'*** domin a cikinta ne labarin '*As'habul Kahfi* ' ya zo, wato labarin mutanen Kogo. Duk ilahirin Alƙur'ani babu inda aka ba da labarinsu sai a wannan Sura kaɗai, shi ne dalilin da ya sa ta ci sunansu.
Kiran wannan Sura da wannan sunan ya zo a cikin ingantattun hadisai na Annabi (ﷺ), kuma shi ne abin da ke rubuce cikin mushafai.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Ibnu Aɗiyya ya kawo cewa, malaman Tafsiri sun haɗu a kan cewa wannan Sura ce *Makkiyya*. Abu Abdullahi Al- Kurɗubi ya goyi bayansa a kan haka.
Amma wasu malamai sun togace aya ta (1) zuwa ta (8) sun ce a Madina aka saukar da su. Wasu kuma suka togace aya ta (28). To amma ingantacciyar magana ita ce, wannan Sura daga farkonta har ƙarshenta *Makkiyya* ce.

3. Jerin Saukarta:
Wannan Sura ita ce ta sittin da takwas (68) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan 'Suratul Gashiya', kafin saukar 'Suratus-Shura'.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Makka da Madina ayoyinta ɗari da biyar ne (105). A lissasfin mutanen Sham kuwa ayoyinta ɗari da shida ne (106). Su kuma mutanen Basra a lissafinsu ɗari da goma sha ɗaya ne (111). Mutanen Kufa kuwa a wurinsu ayoyinta ɗari da goma ne daidai (110). Watau dai an samu saɓani ne wajen tantance farkon wasu ayoyi da ƙarshensu, wasu sai su lissafa aya biyu a matsayin ɗaya, wasu kuma su lissafa aya ɗaya a matsayin biyu.

5. Sababin Saukarta:
Imam Ibnu Jarir ya ruwaito da isnadinsa daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) cewa: "Yayin da Larabawan Kuraishawa suka ga irin yadda Annabi (ﷺ) yake matsa musu da kira zuwa ga imani da Allah, da jan hankalinsu a kan su bi Alƙur'ani, sai suka tura wakilansu Madina wurin Yahudawa domin su yi musu tambaya a kan Annabi (ﷺ) don su ba su wani bayani wanda za su ƙure Annabi (ﷺ) da shi, domin su ma Yahudawa an saukar musu da littafi suna da ilimi. Da suka je sai Yahudawa suka ce musu su koma su yi wa Annabi (ﷺ) tambayoyi uku; idan ya ba su amsarsu daidai, to tabbas shi Annabi ne sai su bi shi; idan kuwa ya kasa ba da amsarsu, to shi ba annabin gaskiya ba ne, daga nan sai su yanke shawarar abin da ya kamata su yi masa. Suka umarce su da su tambaye shi ƙissar *As'habul Kahfi*, da ta Zulƙarnaini, da kuma sha'anin Ruhi, watau rai da yake jikin ɗan'adam.
Waɗannan wakilai suka dawo Makka suka kuma yi wa Annabi (ﷺ) waɗannan tambayoyi, sai ya nemi cewa, su dawo gobe zai ba su amsa. Sai ya manta bai ce *insha Allahu* ba, saboda haka sai aka samu

jinkirin saukar wahayi na kimanin kwana goma sha biyar. Wannan kuwa ya sa Annabi (ﷺ) ya shiga matuƙar damuwa, kuma aka yi ta yayata maganganu a cikin garin Makka cewa, aljanin da yake kawo wa Annabi (ﷺ) labarai shi ma ya watsar da shi. Daga baya Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar masa da wannan Sura, wadda a cikinta ya ba shi tarbiyyar cewa, kada ya sake cewa zai yi wani abu gobe ba tare da ya haɗa da *insha Allahu* ba".
Wannan ruwaya mai rauni ce, a cikin sanadinta akwai mai ruwayan da ba a bayyana kowane ne shi ba. Amma duk da haka wasu malaman sukan ambaci wannan ƙissar.

6. Falalar Surar:
Hadisai ingantattu sun tabbata daga Annabi (ﷺ) game da falalar karanta *Suratul Kahfi*:
An karɓo daga Albara'u ɗan Azib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wani mutum yana karanta *Suratul Kahfi* a cikin gidansa, a lokacin kuwa dokinsa yana ɗaure, sai ya riƙa zabura yana firgita. Da ya fito domin ya ga abin da yake faruwa, sai ya ga wani girgije ne ya yiwo ƙasa-ƙasa ya lulluɓe nahiyar gidansa. Washe-gari ya je ya faɗa wa Annabi (ﷺ) abin da ya faru, sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Ka ci gaba da karatunka wane, domin wannan natsuwa ce take sauka domin karatun Alƙur'ani." [Bukhari #3614 da Muslim #795].
Wannan mutum shi ne Usaidu ɗan Hudhair, kamar yadda ya zo a wasu ruwayoyi.

An karɓo daga Abud-Darda'i (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) yana cewa: "Duk wanda ya haddace ayoyi goma na farkon Suratul Kahfi to za a tsare shi daga fitinar Dujal." [Muslim #809].

A wani lafazin kuma: "Ayoyi goma na ƙarshe na *Suratul Kahfi*". Amma lafazin farko shi ne ya inganta. [Duba Ibnul Kayyim, *Jala'ul Afham*, shafi na 325].
Watau idan Dujal ya bayyana to shi mutumen zai samu kariya a dalilin waɗannan ayoyi guda goma da ya haddace.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa:
• Wannan Sura ta sauka a Makka daidai lokacin da ake nuna wa Annabi (ﷺ) da sahabbansa tsananin ƙiyayya da gaba, har wasu daga cikinsu suka yi gudun hijira zuwa Habasha. Ana cikin irin wannan yanayi wannan Surar ta sauka, domin ta karantar da Annabi (ﷺ) da sahabbansa cewa, su yi haƙuri, haka sha'anin addini ya gada. Allah Ta'ala kuma ya halicci rayuwa ne gaba ɗaya don ya jarraba ɗan'adam ya ga wane ne zai tsaya ya kyautata aikinsa.
• Surar ta kuma ba da misali na wasu da suka tsinci kawunansu cikin fitina amma suka riƙe Allah suka dogara gare shi, kuma ya kuɓutar da su daga wannan fitinar. Su ne *As'habul Kahfi* waɗanda suka taso a garin da ba imani a cikinsa, amma Allah Ta'ala ya sa duk da haka suka iya rinjayar zukatansu, suka kuma rinjayi fitinar da suka samu kawunansu a ciki, Allah ya ba su nasara ya tsare su.
• A wannan Sura, Allah Ta'ala ya lallashi Annabi (ﷺ) yayin da ya shiga damuwa dangane da mutanensa da suka ƙi amsar gaskiyar da ya zo musu da ita, ya nuna masa kada ya damu, domin ya halicci mutane ne daban-daban, kuma ya yi su don ya jarraba su, a cikin su akwai wanda zai ci jarrabawar, akwai kuma wanda ba zai ci ba. Don haka waɗanda Allah ya ga dama ya shiryar daga cikinsu za su shiriya kamar yadda ya shiryar da samarin *As'habul Kahfi*.
• Haka kuma Surar ta yi bayanin yadda Iblis ya nuna wa mutum na farko ƙiyayya shi da zurriyyarsa. Ta bayyana cewa duk wani ruɗi na duniya da yaudarar ƙyale-ƙyalenta daga Shaiɗan ne, don haka mutane kada su bari ya ruɗe su ya hana su samun rabauta ta duniya da lahira.
• Surar ta zo da faɗakarwa dangane da wanda zai ruɗu da iliminsa, inda ta tarbiyyanci mutane a kan su san cewa, duk inda mutum ya kai ga ilimi to ilimin Allah ya fi nasa, Allah kuma zai iya sanya abin da bai sani ba a hannun wani na ƙasa da shi, kamar yadda ƙissar Annabi Musa da Khadir ta nuna.
• Surar ta ja hankali a kan wanda zai ruɗu don Allah ya mallaka masa wani mulki na duniya, har ya kai shi ga bijire wa Allah, ko ya kai shi ga zalunci a bayan ƙasa. Kissar Zulƙarnaini ta bayyana mana wannan. Duk

da ɗimbin ilimi da mulki da Allah ya ba shi, ya shiga lunguna-lunguna na duniya da ƙarfin ikonsa, amma hakan bai sa ya zalunci wani ba, hakan kuma bai sa shi ya bijire wa Allah ba. Ya yi amfani da ƙarfn mulkin da Allah ya ba shi wajen tabbatar da gaskiya da adalci.

• Surar dai ta zo da misalai na wasu abubuwa kishiyoyin juna. Ta yi bayanin alhairi, ta kuma yi bayanin sharri; ta yi bayanin imani, kuma ta yi bayanin kafirci; ta yi bayanin adalci, ta kuma yi bayanin zalunci; haka kuma ta yi bayanin waɗanda suka yi imani, Allah kuma ya ƙara musu shiriya, da kuma waɗanda suka kafirce wa Allah. Wannan duka don ta ɗora mutum a kan tarbiyyar da za ta sanya shi ya ci jarrabawar da Allah ya shirya masa

Suratul Kahf (1-8)

ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ عَلَىٰ عَبۡدِهِ ٱلۡكِتَٰبَ وَلَمۡ يَجۡعَل لَّهُۥ عِوَجَاۜ ١ قَيِّمٗا لِّيُنذِرَ بَأۡسٗا شَدِيدٗا مِّن لَّدُنۡهُ وَيُبَشِّرَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٱلَّذِينَ يَعۡمَلُونَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمۡ أَجۡرًا حَسَنٗا ٢ مَّٰكِثِينَ فِيهِ أَبَدٗا ٣ وَيُنذِرَ ٱلَّذِينَ قَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدٗا ٤ مَّا لَهُم بِهِۦ مِنۡ عِلۡمٖ وَلَا لِأٓبَآئِهِمۡۚ كَبُرَتۡ كَلِمَةٗ تَخۡرُجُ مِنۡ أَفۡوَٰهِهِمۡۚ إِن يَقُولُونَ إِلَّا كَذِبٗا ٥ فَلَعَلَّكَ بَٰخِعٞ نَّفۡسَكَ عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِمۡ إِن لَّمۡ يُؤۡمِنُواْ بِهَٰذَا ٱلۡحَدِيثِ أَسَفًا ٦ إِنَّا جَعَلۡنَا مَا عَلَى ٱلۡأَرۡضِ زِينَةٗ لَّهَا لِنَبۡلُوَهُمۡ أَيُّهُمۡ أَحۡسَنُ عَمَلٗا ٧ وَإِنَّا لَجَٰعِلُونَ مَا عَلَيۡهَا صَعِيدٗا جُرُزًا ٨

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Dukkan yabo ya tabbata ga Allah wanda Ya saukar wa da Bawansa Littafi, bai kuma sanya masa wata karkata ba.

2. Daidaitacce ne, don ya yi gargaɗi game da azaba mai tsanani daga gare Shi (wato Allah), ya kuma yi wa muminai waɗanda suke aiki nagari albishir cewa suna da lada kyakkyawa.

3. Madawwama a cikinsa har abada.

4. Ya kuma gargaɗi waɗanda suka ce Allah Yana da ɗa.

5. Ba su da wani ilimi game da shi (wannan zance) kuma iyayensu ma ba su da (ilimi game da shi). Kalmar da take fitowa daga bakunansu ta yi girma. Ba abin da suke faɗa sai ƙarya.

6. To ko mai yiwuwa ne za ka kashe kanka da baƙin ciki, in ba su yi imani da wannan zancen ba (watau Alƙur'ani).

7. Lalle Mu Mun sanya abin da yake bayan ƙasa ya zama ado a gare ta, don (kuma) Mu jarraba su, wane ne daga cikinsu ya fi kyakkyawan aiki?

8. Lalle kuma Mu za Mu mai da abin da yake kanta (ya zama) turɓaya ƙeƙasasshiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da godiya da yabo da kirari ga Zatinsa don ya tabbatar da cewa, shi ne ya fi kowa cancantar duk wata sifa ta ɗaukaka da kamala. Ya bayyana cewa, shi ne wanda ya saukar wa da bawansa Annabi Muhammadu (ﷺ) Alƙur'ani wanda ba shi da wata tawaya ta kowace fuska. Ya sanya shi littafi ne daidaitacce wanda babu tufka-da-warwara a cikinsa domin ya tsoratar da kafirai da shi game da wata azaba mai tsanani daga Allah da take jiran su a lahira idan ba su yi imani da Allah da Manzonsa ba. Hakanan kuma ya yi wa muminai waɗanda suka yi ayyuka na ƙwarai

albishirin samun wani kyakkyawan sakamako da babu kamarsa, wanda shi ne gidan Aljanna. Za su zauna har abada a cikin wannan sakamako ba zai yanke musu ba.
Sannan kuma ya gargaɗi kafirai waɗanda suke cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da ɗa, su ne Yahudu da Nasara har ma da mushirikan Larabawa masu cewa mala'iku 'ya'yan Allah ne mata. Ya bayyana cewa masu irin wannan ƙagen ga Allah ba su da wani ilimi ko wani dalili da suka dogara da shi a kan da'awarsu. Kai har ma iyayensu da suke koyi da su ba su da wani ilimi a kan wannan lamari da suke da'awa. Allah ya bayyana cewa, magana mummuna da take fitowa daga bakunansu ta yi matuƙar muni. Ba komai suke furtawa ba kuma sai ƙarya zunzurutunta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da lallashin Manzonsa (ﷺ) wanda rashin yin imanin kafirai yake matuƙar damunsa. Ya nuna masa cewa, kada ya kashe kansa da yawan damuwa da yake sakawa a ransa don mutanensa sun ƙi yin imani da Alƙur'ani, domin shiriyarsu ba a hannunsa take ba.
Sai kuma ya bayyana masa cewa, duk wani abu da ya halitta a doron ƙasa ya yi shi ne don jarrabawa don ya tantance waɗanda suka fi kyakkyawan aiki daga cikin bayinsa. Kuma daga ƙarshe duk wani ƙyale-ƙyale da yake bayan ƙasa zai mayar da shi turɓaya ƙeƙasasshiya wadda babu wani tsiro a kanta. Don haka ya daina damuwa da abin da zai gani ko zai ji daga maƙiyansa domin kowa daga ƙarshe zai koma ne ga Allah ya yi wa kowa hisabi a kan abin da ya aikata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Labarin mutanen kogo yana daga cikin abubuwan mamaki domin yana nuna isar Ƙudurar Allah wajen tayar da matattu.

2. Halaccin gujewa da addini da yin hijira da barin iyali, domin guje wa fitina.

3. An keɓe kunnuwansu da ambato domin kunne shi ne gaɓar da ta hanyarta ne sau tari barci yake yankewa. Don haka barci ba zai iya ƙarfi ba har sai an dakatar da aikin kunnuwa. Yana daga cikin ambaton kunne a barci hadisin da aka ruwaito daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce:

"An faɗa wa Manzon Allah (ﷺ) labarin wani mutum da idan ya kwanta barci ba ya tashi har sai gari ya waye, sai ya ce: 'Wannan mutum ne da Shaiɗan ya yi masa fitsari a kunnuwansa'." [Bukhari #1144 da Muslim #774].

4. Ƙungiyoyi biyu da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata game da sanin adadin shekarun da mutanen kogo suka yi suna barci, magana mafi rinjaye ita ce: Ƙungiya ta farko su ne waɗannan samarin waɗanda suka zaci cewa barcinsu ya kasance ne na ɗan lokaci kaɗan. Ƙungiya ta biyu, su ne mutanen gari waɗanda aka tashi samarin a zamaninsu waɗanda ya zamanto suna da tarihin al'amarin waɗannan samarin. Wannan ita ce maganar yawancin malaman tafsiri.

Suratul Kahf (9-12)
أَمْ حَسِبْتَ أَنَّ أَصْحَٰبَ ٱلْكَهْفِ وَٱلرَّقِيمِ كَانُوا۟ مِنْ ءَايَٰتِنَا عَجَبًا ﴿٩﴾ إِذْ أَوَى ٱلْفِتْيَةُ إِلَى ٱلْكَهْفِ فَقَالُوا۟ رَبَّنَآ ءَاتِنَا مِن لَّدُنكَ رَحْمَةً وَهَيِّئْ لَنَا مِنْ أَمْرِنَا رَشَدًا ﴿١٠﴾ فَضَرَبْنَا عَلَىٰٓ ءَاذَانِهِمْ فِى ٱلْكَهْفِ سِنِينَ عَدَدًا ﴿١١﴾ ثُمَّ بَعَثْنَٰهُمْ لِنَعْلَمَ أَىُّ ٱلْحِزْبَيْنِ أَحْصَىٰ لِمَا لَبِثُوٓا۟ أَمَدًا ﴿١٢﴾

9. Shin ka yi tsammanin cewa lalle Mutanen Kogo da Raƙimu sun kasance daga ayoyinmu masu ban mamaki?

10. Lokacin da samarin nan suka fake a Kogon, sai suka ce: “Ya Ubangijinmu, Ka ba mu rahama daga gare Ka, Ka kuma tanadar mana shiriya cikin lamarinmu.

11. Sai Muka sanya (shamaki) a kan kunnuwansu (suka yi barci) shekaru masu yawa a cikin Kogon.

12. Sannan Muka tashe su don Mu san wane ne daga ƙungiyoyin nan biyu (masu saɓani game da lamarin samarin) ya fi kiyayewa da tsawon zamaninsu?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yin shimfiɗa ne a kan labarin mutanen kogo, yana tabbatar wa da Annabi (ﷺ) cewa, labarinsu yana ƙunshe da abin mamaki kamar yadda yake zato. Duk kuwa da cewa akwai wasu abubuwa da suka fi shi ban mamaki kamar halittar sammai da ƙasa da sassaɓawar rana da wata.
Mutanen kogo wasu samari ne ‘ya’yan sarakunan Rumawa da manyan gari waɗanda suka lura da cewa, abin da mutanensu suke yi na bautar wanin Allah da yin sujjada ga gumaka ɓarna ce ba daidai ne ba, don haka sai suka ware kansu waje guda suka riƙa bautar Allah shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba. Suna cikin haka ne wasu suka sami labarinsu sai suka garzaya wajen Sarkinsu suka bayyana masa abin da samarin nan suke ciki.
Wannan Sarki mai suna Daƙayanusa wani azzalumin mutum ne. Yayin da ya sami labarinsu sai ya aika aka kawo su gabansa, ya umarce su da lalle su kafirce wa Allah su dawo kan bautar gumakansu, amma waɗannan samari suka taurare masa. Allah kuwa ya ƙara musu ƙarfin imani. Wannan ya sa sarkin ya yi yunƙurin hallaka su gaba ɗayansu, sai suka gudu suka shiga wani kogo suka ɓuya a cikinsa. Suka roƙi Allah da ya ba su wata rahama daga gare shi ya kuma tanadar musu shiriya cikin lamarinsu. To a nan ne Allah ya karɓi roƙonsu ya saka musu wani dogon barci wanda suka share shekaru masu yawa suna yin sa har zuwa wani lokaci da Allah ya ga damar tayar da su don ya tabbatar wa da mutane gaskiyar yiwuwar tashin matattu domin hisabi kuma ya bayyana wane ne a cikin ƙungiyoyi biyu masu saɓani a cikin lamarinsu ya fi kiyaye lissafin shekarun da suka yi suna barci.
Game da adadinsu bayani zai zo a aya ta 22, amma game da sunayensu babu wani abin da ya inganta a kan hakan. Sannan sanin sunayensu ba wani abu ne mai muhimmanci ba.
Arraƙimu kuwa da Allah ya ambata a nan malamai sun yi saɓani wajen tantance shi:
• Wasu sun ce shi ne dutsen da kogon da samarin suka ɓoye yake jiki.
• Wasu kuma sun ce shi ne allon da aka rubuta sunayensu a kai.
• Amma kuma wasu malamai sun ce Arraƙimu shi ne labarin mutanen nan uku da suka shiga kogon dutse ya rufe da su, kowane ɗaya daga cikinsu ya yi tawassuli da wani aikin ƙwarai da ya taɓa yi don Allah, ya roƙi Allah da shi, har Allah ya buɗe musu ƙofar wannan kogon suka kuɓuta daga halaka. Imamul Bukhari ya zaɓi wannan ra’ayi na ƙarshe.
Imamu Ahmad (#18417) da Ɗabarani (*Al-Ma’jamu’ul Kabir*, juzu’i na 2, shafi na 206) sun ruwaito da kyakkyawan isnadi daga An-Nu’uman ɗan Bashiru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, ya ji Manzon Allah (ﷺ) ya ambaci Arraƙimu sai ya ce: “Lalle an sami wasu mutane su uku da suka kasance a cikin kogo sai dutse ya gangaro ya rufe musu ƙofar kogon....” Har zuwa ƙarshen hadisin.
Game da addinin da samarin suke bi, wasu malamai sun ce suna bin addinin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne. To amma wannan ra’ayi yana da rauni, domin da a ce addinin Annabi Isa suke bi da Yahudawa ba su ɗauki al’amarinsu da muhimmanci ba. Sai dai sun rayu ne gabanin zuwan Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Labaran da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar a cikin Alƙur’ani duk na gaskiya ne, babu sofanen ƙarya ko kokwanto a cikinsu.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗannan mutane samari ne, saboda a koyaushe samari sun fi dattawa da tsofaffi sauraron gaskiya da karɓar ta. Don haka ne ma waɗanda suka fi amsa kiran Manzon Allah (ﷺ) a lokacinsa samari ne. Amma dattawan Ƙuraishawa da damansu sun mutu ne ba su musulunta ba.

3. Imani yana ƙaruwa da ƙaruwar ayyukan ɗa'a ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Tsayuwar samarin a gaban azzalumin sarki kafiri su faɗa masa gaskiya dalili ne da yake nuna ƙarfin imaninsu da ikhlasinsu da dogaronsu ga Allah shi kaɗai.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karɓi addu'arsu ya sanya rahamarsa da kariyarsa gare su. Don haka suka ƙare zamansu a cikin wannan kogo ba tare da mutanensu sun gano inda suke ba, duk da cewa wannan kogo ba ya da nisa daga garinsu kamar yadda aya ta 19 take nunawa.

Suratul Kahf (13-16)

نَّحۡنُ نَقُصُّ عَلَيۡكَ نَبَأَهُم بِٱلۡحَقِّۚ إِنَّهُمۡ فِتۡيَةٌ ءَامَنُواْ بِرَبِّهِمۡ وَزِدۡنَٰهُمۡ هُدٗى ١٣ وَرَبَطۡنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ إِذۡ قَامُواْ فَقَالُواْ رَبُّنَا رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ لَن نَّدۡعُوَاْ مِن دُونِهِۦٓ إِلَٰهٗاۖ لَّقَدۡ قُلۡنَآ إِذٗا شَطَطٗا ١٤ هَٰٓؤُلَآءِ قَوۡمُنَا ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةٗۖ لَّوۡلَا يَأۡتُونَ عَلَيۡهِم بِسُلۡطَٰنِۭ بَيِّنٖۖ فَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبٗا ١٥ وَإِذِ ٱعۡتَزَلۡتُمُوهُمۡ وَمَا يَعۡبُدُونَ إِلَّا ٱللَّهَ فَأۡوُۥٓاْ إِلَى ٱلۡكَهۡفِ يَنشُرۡ لَكُمۡ رَبُّكُم مِّن رَّحۡمَتِهِۦ وَيُهَيِّئۡ لَكُم مِّنۡ أَمۡرِكُم مِّرۡفَقٗا ١٦

13. Mu ne za Mu ba ka labarinsu da gaskiya. Lalle su samari ne da suka yi imani da Ubangijinsu, Muka kuwa ƙara musu shiriya.

14. Muka kuma ɗaure zukatansu lokacin da suka tsaya suka ce: "Ubangijinmu Shi ne Ubangijin sammai da ƙasa; ba za mu bauta wa wani abin bauta ba in ban da Shi; idan muka yi haka kuwa to haƙiƙa mun faɗi ƙarya.

15. "Waɗannan mutanenmu ne da suka riƙi wasu alloli ba Shi ba; me ya hana ba su zo musu da wata hujja mabayyaniya (kan haka) ba? To ba wanda ya fi zalunci fiye da wanda ya yi wa Allah ƙarya.

16. "Tun da kun ƙaurace musu tare da abin da suke bauta wa sai Allah, to sai ku tare a kogon, Ubangijinku zai yalwata muku rahamarsa ya kuma shirya muku hanyar rayuwa mai sauƙi ga al'amuranku."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shiga fayyace ƙissar mutanen kogo, inda ya bayyana cewa, zai ba wa Annabi (ﷺ) labarinsu da gaskiyar da babu kokwanto a cikinta, da cewa, su samari ne waɗanda suka yi imani da Ubangijinsu suka yarda da shi kaɗai ne abin bauta suka kuma dage da yi masa ɗa'a, sai ya ƙara musu shiriya da tabbata a kan gaskiya. Ya kuma ƙarfafi zukatansu da imani suka samu juriya da haƙuri da rashin tsoro ko fargaba, yayin da suka tsaya gaban sarkinsu kafiri, azzalumi, suka bayyana masa imaninsu da Allah mahaliccin sammai da ƙasa tare da tabbatar masa cewa, ba za su ƙara yarda su bauta wa wani ba shi ba, domin idan har sun yi haka to sun faɗi maganar ƙarya ke nan ba gaskiya ba.

A kan haka waɗannan samari suka bar jama'arsu suka koma waje ɗaya suna tattaunawa tsakaninsu da junansu cewa, mutanensu sun riƙi wasu gumaka suna bauta musu ba Allah ba, duk da cewa kuwa ba su da

wata hujja bayyananniya a kan haka. Suka tabbatar wa juna cewa babu azzalumi kamar wanda ya ƙaga wa Allah ƙarya ya ce yana da abokin tarayya. Suka zartar da cewa, yanzu kam tun da sun ƙaurace wa mutanensu sun bar abin da suke bauta wa ba Allah ba, to kamata ya yi su gudu su ɓuya a cikin kogo, da fatan Allah zai shimfiɗa musu rahamarsa ya tsare su daga abokan gabarsu, ta yadda ba za su gan su ba, kuma ya shirya musu abin da duk za su buƙata na rayuwa a cikin wannan kogon, su sami hutu da yalwar rayuwa ba tare da sun koma cikin mutanensu ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karamar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bai wa mutanen kogo.

2. Rana tana tafiya a sararin samaniya ba a tsaye take cak ba.

3. Rarrashin Annabi (ﷺ) a kan yawan damuwa da yake yi don mutanensa sun ƙi yin imani, ta hanyar yi masa bayani cewa, shiriya ba a hannunsa take ba, tana hannun Allah ne. Wanda ya ga damar shiryarwa zai shiryar da shi, wanda kuwa ya zaɓi ɓata to babu wanda zai iya shiryar da shi ba Allah ba.

4. Allah ya riƙa jujjuya samarin hagu da dama, amma ba a ambaci bayansu da cikunkunansu ba, domin yin barci ta ɓangaren dama ko ta ɓangaren hagu ya fi a kan kwanciya rigingine ko rub-da-ciki.

5. Ayar Allah da ke tattare a cikin barcinsu na tsawon shekaru da tsare rayuwarsu ba tare da ci ko sha ba, ya fi ban mamaki fiye da tsare su daga zafin rana ko canjawar da ƙasa take yi ga jikinsu.

6. Wasu malamai sun ce, hikimar da ke cikin jujjuya su dama da hagu, don taimaka wa gudanar jini a duk sassan jikinsu ne; domin da a ce a ɓangare ɗaya suke kwance na tsawon wannan lokaci to da ɗaya ɓarin jikinsu na sama ya ruɓe saboda rashin samun isasshen jini da zai yi, duk kuwa da cewa Allah mai iko ne a kan komai.
Wasu kuma sun ce jujjuya su da Allah ya yi karama ce a gare su, domin hakan bai faru ga karensu ba. Wannan ya nuna cewa jujjuyawar ba ta da alaƙa da kuɓutar gangar jikinsu daga lalacewa.

7. Wanda duk ya so mutanen kirki zai sami falalarsu da albarkarsu. Domin ga kare ma ya sami albarkacin wannan samari har Allah ya ambace shi a littafinsa Alƙur'ani. Don haka mutum yana tare da masoyansa ne har ranar alƙiyama.

Suratul Kahf (17-18)
*وَتَرَى ٱلشَّمۡسَ إِذَا طَلَعَت تَّزَٰوَرُ عَن كَهۡفِهِمۡ ذَاتَ ٱلۡيَمِينِ وَإِذَا غَرَبَت تَّقۡرِضُهُمۡ ذَاتَ ٱلشِّمَالِ وَهُمۡ فِي فَجۡوَةٖ مِّنۡهُۚ ذَٰلِكَ مِنۡ ءَايَٰتِ ٱللَّهِۗ
مَن يَهۡدِ ٱللَّهُ فَهُوَ ٱلۡمُهۡتَدِۖ وَمَن يُضۡلِلۡ فَلَن تَجِدَ لَهُۥ وَلِيّٗا مُّرۡشِدٗا ١٧ وَتَحۡسَبُهُمۡ أَيۡقَاظٗا وَهُمۡ رُقُودٞۚ وَنُقَلِّبُهُمۡ ذَاتَ ٱلۡيَمِينِ وَذَاتَ ٱلشِّمَالِۖ وَكَلۡبُهُم
بَٰسِطٞ ذِرَاعَيۡهِ بِٱلۡوَصِيدِۚ لَوِ ٱطَّلَعۡتَ عَلَيۡهِمۡ لَوَلَّيۡتَ مِنۡهُمۡ فِرَارٗا وَلَمُلِئۡتَ مِنۡهُمۡ رُعۡبٗا ١٨

17. (Sai) kuma ka ga rana idan za ta ɓullo tana kauce wa kogonsu ta ɓangaren dama, idan kuma za ta faɗi sai ta riƙa kauce musu ta ɓangaren hagu, su kuwa suna tsakiyarsa. Wannan yana daga ayoyin Allah. Wanda Allah Ya shiryar to shi ne shiryayye, wanda kuwa Ya ɓatar to ba za ka sami wani majiɓinci da zai shirye shi ba.

18. Za kuma ka zaci a farke suke alhali kuwa suna bacci ne. Muka kuma riƙa juya su ta ɓarin dama da kuma ta ɓarin hagu; karensu kuwa ya shimfiɗa ƙafafunsa na gaba a mashigar kogon. Da abin ka leƙa su ne to lalle da ka fita a guje, lalle kuma da ka cika da tsoron su.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana irin tanadin da ya yi wa samarin nan a wannan kogon, ya samar musu wani yanayi da babu abin da zai cutar da su. Rana idan ta fito tana karkace wa kogonsu ta ɓangaren dama, idan kuma ta zo faɗuwa sai ta karkace masa ta ɓangaren hagu.
Malam Ibnu Kasir ya ce: "Wannan ya nuna cewa ƙofar shiga kogon tana ɓangaren hagu ne, domin Allah ya bayyana cewa idan rana ta shigo cikinsa lokacin hudowarta tana karkace masa ta ɓangaren dama, watau inuwarsa tana janyewa ta dama, saboda duk sa'adda za ta ƙara yin sama to haskenta yana ƙara raguwa har ya kai lokacin da zai gushe gaba ɗaya yayin da rana ta yi zawali. Don haka ne ma Allah ya ce: 'Idan ta zo faɗuwa tana kauce musu ta ɓangaren hagu.' Watau dai rana tana shiga kogonsu ne ta hagun ƙofarsa, watau nahiyar gabas. Wannan ya tabbatar da abin da muka ambata..."
Su kuma samarin suna tsakiyar kogon a kwance suna samun iskar shaƙa yadda ya kamata. Da haka Allah ya tsare gangar jikinsu da tufafinsu ba abin da ya same su tsawon shekarun da suka yi suna barci a wannan kogo.
Allah ya bayyana cewa duk waɗannan abubuwa da ya yi suna cikin ayoyinsa ne masu nuna cikar ikonsa a kan komai. Don haka duk wanda ya shiryar da shi ga hanyar shiriya shi ne shiryyaye, wanda kuwa ya ɓatar da shi to ba za ka sami wani mai shiryar da shi ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata baiwar da ya yi wa waɗannan samari lokacin da suke kwance suna barci a wannan kogo. Watau shi ne yadda idan mutum ya gan su sai ya zaci a farke suke ba barci suke yi ba, domin suna yin barcin zomo ne, idanuwansu duka a buɗe suke. Kuma Allah ya riƙa jujjuya su dama da hagu don kada ƙasa ta ci jikkunansu da tufafinsu. Shi kuma karensu da yake tare da su yana kwance ya shimfiɗa ƙafafunsa a gaban mashigar kogon. A daidai wannan lokaci da a ce mutum zai leƙa su ya yi arba da su to da ya fita a guje ya kuma cika da tsoron su, saboda kwarjini da Allah ya zuba musu, domin ba su ƙarin kariya daga mutane.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tashi samarin don ya nuna musu darajar da ya ba su, kuma su ƙara tabbatar da cewa alƙiyama gaskiya ce.

2. Waliyyin Allah yana iya yin kuskure a cikin zatonsa.

3. Yana daga cikin ladabi mutum ya mayar da ilimin abin da ya rikice masa ko bai san shi ba zuwa ga Allah.

4. Aiken ɗaya daga cikin samarin zuwa cikin gari ya samo musu abinci ya ƙara tabbatar da cewa, kogon da suke ciki ba nesa yake daga garinsu ba.

5. Ya halatta mutum ya nemi abinci mai daɗi mai gina jiki lafiyayye na halal.

6. Bayanin cewa, tawakkali shi ne riƙo da sabubba tare da mayar da al'amari zuwa ga Allah. Don haka ne suka umarci ɗan aiken da ya yi taka-tsantsan wajen shiga da fita daga wannan gari don kada wani ya gane shi.

Suratul Kahf (19-20)

وَكَذَٰلِكَ بَعَثۡنَٰهُمۡ لِيَتَسَآءَلُواْ بَيۡنَهُمۡۚ قَالَ قَآئِلٞ مِّنۡهُمۡ كَمۡ لَبِثۡتُمۡۖ قَالُواْ لَبِثۡنَا يَوۡمًا أَوۡ بَعۡضَ يَوۡمٖۚ قَالُواْ رَبُّكُمۡ أَعۡلَمُ بِمَا لَبِثۡتُمۡ فَٱبۡعَثُوٓاْ أَحَدَكُم
بِوَرِقِكُمۡ هَٰذِهِۦٓ إِلَى ٱلۡمَدِينَةِ فَلۡيَنظُرۡ أَيُّهَآ أَزۡكَىٰ طَعَامٗا فَلۡيَأۡتِكُم بِرِزۡقٖ مِّنۡهُ وَلۡيَتَلَطَّفۡ وَلَا يُشۡعِرَنَّ بِكُمۡ أَحَدًا ١٩ إِنَّهُمۡ إِن يَظۡهَرُواْ عَلَيۡكُمۡ
يَرۡجُمُوكُمۡ أَوۡ يُعِيدُوكُمۡ فِي مِلَّتِهِمۡ وَلَن تُفۡلِحُوٓاْ إِذٗا أَبَدٗا ٢٠

19. Kamar haka Muka tashe su don su riƙa tambayar junansu. Wani mai tambaya daga cikinsu ya ce: "Mene ne tsawon zamanku (a nan)?" Suka ce: "Mun yi zaman yini ɗaya ne ko kuma rabin yini." (Sannan kuma) suka ce: "Ubangijinku ne Ya fi sanin tsawon zaman da kuka yi, sai ku aiki ɗayanku da wannan kuɗin naku cikin gari, sai ya duba ya ga wanne irin abinci ne ya fi tsarki, to sai ya zo muku da abin da za ku ci da shi (kuɗin), kuma ya yi taka-tsantsan kada wani ya shaida ku.
20. "Lalle idan suka yi galaba a kanku to za su jefe ku ko kuma su mai da ku cikin addininsu, to shi ke nan ba za ku rabauta ba har abada."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda ya nuna abubuwan mamakinsa game da waɗannan samari, to hakanan kuma ya tashe su daga dogon barcinsu don su yi wa juna tambaya a kan tsawon lokacin da suka share suna barci. Sai wasu daga cikinsu suka ce, ai sun yi barci ne kawai na yini guda ko ma rabin yini, domin sun shiga wannan kogo ne da safe sai kuma suka farka da yamma. To amma kuma sai wasu daga cikinsu suka ce Allah ne dai kawai ya san tsawon lokacin da suka share suna wannan wuri, don haka su mayar masa da alʾamarinsu su dawo da tunaninsu a kan abin da ya fi musu muhimmanci, shi ne nemo abin da za su ci, domin suna cikin matuƙar yunwa. Don haka sai suka yi shawarar su aika ɗaya daga cikinsu ya shiga gari ya nemo musu abinci, suka ba shi kuɗin azurfa da ke tare da su lokacin da suka shiga kogo. Suka kuma jaddada masa cewa, ya tabbatar ya sayo musu abinci na halal, kada ya kawo musu abin da bai halatta ba. Suka kuma ja kunnensa da cewa, ya yi taka-tsantsan wajen shiga wannan garin da wajen fitowa da wajen muʾamalarsa da abokan cinikinsa, kada ya bari wani ya gane inda suka ɓoye, domin idan mutanen garin suka fahimci inda suka ɓoye to za su zo su kama su su je su jefe su har su mutu, ko kuma su tursasa musu komawa ga gurɓataccen addininsu wanda Allah ya so su da shiriya suka bar shi zuwa ga addinin gaskiya. Suka tabbatar wa da juna cewa idan kuwa har suka yarda suka koma tsohon addininsu to ba za su rabauta ba har abada a duniya da lahira.
Daga nan wannan ɗan aike ya fita ya nufi hanyar shiga gari; to tun daga nan ya fara ganin canje-canje waɗanda bai san da su ba lokacin da suka fita daga gari. Mamaki ya rufe shi na ganin gagarumin canji. Ta yaya ya faru a ɗan ƙanƙanin lokaci irin wannan? Bai san cewa bayan fitarsu an yi al'ummu daban-daban sun zo sun shuɗe, komai na garin ya canja daga yadda ya san shi a baya. Yana isowa ƙofar shiga gari kuma ya ga alamun Musulunci a ƙofar garin. Ya sake ruɗewa. Ya shiga kasuwa ya miƙa kuɗinsa domin a ba shi gurasa. Da mai gurasa ya ga wannan tsohon kuɗin sai ya tambaye shi ina ya sami irin wannan kuɗin? Nan take rigima ta kaure tsakaninsu, domin mai gurasa ya zargi wannan saurayi da ya tsinci wata tsohuwar taska ce ta kuɗi, don haka lalle sai ya nuna masa inda ya samo ta. Rigima ta kai su har gaban Sarki, inda daga ƙarshe aka gano cewa, wannan saurayi ɗaya ne daga cikin samarin da tarihi ya nuna sun taɓa fita daga wannan garin sun guje wa wani azzalumin sarki wanda ya nemi sai sun yi kafirci. Daga nan Sarkin ya yi umarni a tasa wannan saurayi gaba har sai ya kai su kogon da 'yanʾuwansa suke ciki. Da suka isa bakin kogo ya roƙi jamaʾa da kada su shiga domin za su tsoratar da 'yanʾuwansa; su bari shi ya shiga don ya sanar da su abin da ake ciki. Yana shiga kuwa sai suka ji shiru bai sake fitowa ba. Waɗannan samari sun roƙi Allah ya karɓi rayukansu a wannan lokacin. Allah kuwa ya karɓi addu'arsu ya karɓi rayukansu gaba ɗaya. [Dubi, Ibnu Hajar, *Taghliƙut Taʾaliƙ*, Juzuʾi na 4, shafi na 246] Daga Ibnu Abbas (Allah ya kara masa yarda).

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Malamai da yawa sun ce: Mutane a wancan zamani sun kasance suna musu game da tashin alƙiyama, shin Allah zai tashi ruhi ne kawai, ko kuma zai tashi ruhi ne tare da gangar jiki? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu mutanen kogo waɗanda suka share shekara har ɗari uku ko ɗari uku da tara suna barci, ba ci ba sha, amma daga ƙarshe Allah ya tashe su da gangar jikinsu. Wannan ya ƙara tabbatar da cewa, Allah zai tashi mutane ne da gangar jikinsu domin yi musu hisabi.

2. Masu sabani game da abin da za a yi wa samarin kashi biyu ne. Kaso na farko su ne masu rauni waɗanda ba su da komai na iko a hannunsu, to amma sun yi maganar da take nuna su ne masu ilimi da addini a garin. Ɓangare na biyu kuwa su ne masu ƙarfin iko a hannunsu, don haka Allah ya siffanta su da 'rinjaye', kuma maganarsu tana nuna cewa, su mutane ne masu ji da isa, kuma babu abin da zai gagare su aikatawa. Musulunci ya hana gina masallaci a maƙabarta kamar yadda ya hana salla a kan ƙabari ko ana fuskantar sa.

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Lokacin da mutuwa ta zo wa Manzon Allah (ﷺ) ya riƙa rufa mayafi a fuskarsa, idan ya lulluɓa da shi kuma wani lokaci sai ya yaye. Yana cikin haka yake cewa,: "La'anar Allah ta tabbata a kan Yahudawa da Nasara, sun mayar da ƙaburburan annabawansu masallatai." Yana gargaɗin (al'ummarsa) game da abin da suka aikata. [Bukhari #436 da Muslim #531].

An karɓo daga Ummu Habiba da Ummu Salama, sun faɗa wa Annabi (ﷺ) labarin wata coci da suka gano a Habasha mai cike da hotuna. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wannan mutanen sun kasance idan wani mutumin kirki ya mutu a cikinsu sai su gina masallaci a kan ƙabarinsa, su yi irin waɗannan hotunan. Waɗannan su ne ashararun halitta a wurin Allah Ta'ala a ranar alƙiyama." [Bukhari #427 da Muslim #528].

An karɓo daga Abu Marsad Al-Ghanawi ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa,: "Kada ku fuskanci maƙabarta ku yi salla, kuma kada ku zauna a kan ƙaburbura." [Muslim #972].

Suratul Kahf (21)
وَكَذَٰلِكَ أَعۡثَرۡنَا عَلَيۡهِمۡ لِيَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ وَأَنَّ ٱلسَّاعَةَ لَا رَيۡبَ فِيهَآ إِذۡ يَتَنَٰزَعُونَ بَيۡنَهُمۡ أَمۡرَهُمۡۖ فَقَالُواْ ٱبۡنُواْ عَلَيۡهِم بُنۡيَٰنٗاۖ رَّبُّهُمۡ أَعۡلَمُ بِهِمۡۚ قَالَ ٱلَّذِينَ غَلَبُواْ عَلَىٰٓ أَمۡرِهِمۡ لَنَتَّخِذَنَّ عَلَيۡهِم مَّسۡجِدٗا ٢١

21. Kamar haka kuwa Muka nuna wa (mutanen nasu) su don su san cewa lalle alƙawarin Allah gaskiya ne, kuma ita alƙiyama babu kokwanto a cikinta, kuma ka tuna lokacin da su (mutanen) suke ta jayayya a tsakaninsu game da al'amarinsu (watau samarin); sai (wasu daga cikinsu) suka ce: "Ku tayar da gini a kansu (wanda zai toshe ƙofar kogon)." Ubangijinsu Shi Ya fi sanin lamarinsu. Waɗanda suka yi rinjaye kan al'amarinsu suka ce: "Lalle tabbas za mu yi masallaci a kansu (watau a kan ƙabarinsu)."

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda ya nuna abubuwan mamaki game da waɗannan samari har suka share tsawon shekaru suna barci sannan daga ƙarshe ya tashe su, to haka kuma ya nuna su ga mutanen garinsu domin ya nuna musu cewa, ranar alƙiyama gaskiya ce, kuma zai tashi halittu duk, da gangar jikinsu da rayukansu.
Sai kuma ya bayyana cewa, mutane sun yi ta saɓani a kan sha'aninsu bayan sun tabbatar da mutuwarsu. Suka shiga tattaunawa da juna a kan abin da ya kamata su yi wa waɗannan bayin Allah. Sai suka kasu gida biyu: Wasu suka ce kawai a gina katanga a ƙofar kogonsu domin ba su kariya da tsaro, a bar al'amarinsu ga Allah, shi ne ya fi kowa sanin halinsu, domin yanayinsu ya nuna su na musamman ne a wurinsa. Sai

masu iko a garin suka ce lalle sai sun gina masallaci a wannan wurin domin ibada, su kuma riƙa tunawa da su da girmamawa.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kyautatuwar idan malami ya ambaci maganganun malamai a kan wani hukunci to ya bayyana wanda ya fi zama daidai, ya kuma nuna wanda yake da rauni daga cikinsu.

2. Bayani a kan rashin dacewar tattaunawa da saɓani a kan mas'alolin da ba su da wani babban muhimmanci a addinin Musulmi ko rayuwarsu.

3. Ladabi ne ga Allah mai matuƙar muhimmanci idan Musulmi ya yi niyyar zai aikata wani abu ya haɗa maganarsa da faɗar *'in sha Allah*', domin komai Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yarda.

4. Idan mutum ya ce zai yi wani abu amma sai ya manta bai ce 'in sha Allahu' ba, to sai ya faɗe ta duk sanda ya tuna.

5. Ambaton Allah yana taimakawa wajen kawar da mantuwa da magance ta.

6. Yana da kyau sosai bawa ya riƙa roƙon Allah shiriya a komai, don Allah ya taimake shi a kan duk abin da ya fi ƙarfinsa.

Suratul Kahf (22-24)
سَيَقُولُونَ ثَلَٰثَةٞ رَّابِعُهُمۡ كَلۡبُهُمۡ وَيَقُولُونَ خَمۡسَةٞ سَادِسُهُمۡ كَلۡبُهُمۡ رَجۡمَۢا بِٱلۡغَيۡبِۖ وَيَقُولُونَ سَبۡعَةٞ وَثَامِنُهُمۡ كَلۡبُهُمۡۚ قُل رَّبِّيٓ أَعۡلَمُ بِعِدَّتِهِم مَّا يَعۡلَمُهُمۡ إِلَّا قَلِيلٞۗ فَلَا تُمَارِ فِيهِمۡ إِلَّا مِرَآءٗ ظَٰهِرٗا وَلَا تَسۡتَفۡتِ فِيهِم مِّنۡهُمۡ أَحَدٗا ٢٢ وَلَا تَقُولَنَّ لِشَاۡيۡءٍ إِنِّي فَاعِلٞ ذَٰلِكَ غَدًا ٢٣ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُۚ وَٱذۡكُر رَّبَّكَ إِذَا نَسِيتَ وَقُلۡ عَسَىٰٓ أَن يَهۡدِيَنِ رَبِّي لِأَقۡرَبَ مِنۡ هَٰذَا رَشَدٗا ٢٤

22. (Wasu) suka riƙa cewa su uku ne na huɗunsu shi ne karensu; (wasu) kuma suna cewa biyar ne na shidansu ne karensu don lalube cikin duhu; (wasu) kuma suna cewa su bakwai ne na takwas ɗinsu kuma karensu ne. Ka ce (da su): "Ubangiji Shi Ya fi sanin yawansu, ba wanda ya san lamarinsu sai 'yan kaɗan." To kada ka yi jayayya game da (al'amarinsu) sai dai a kan abin da yake a fili, kada kuma ka nemi fatawar ɗaya daga cikinsu game da su (samarin).

23. Kada kuma ka ce da kowane abu: "Lalle zan aikata wannan gobe."

24. Sai dai (tare da cewa): '*In sha Allah*'; ka kuma ambaci Ubangijinka idan ka manta, kuma ka ce: "Ina fatan Ubangijina Ya nuna mini abin da ya fi wannan zama shiriya."

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana saɓanin da ma'abota littafi suka yi game da adadin yawan mutanen kogo, inda aka samu wasu suka yi ta faɗar maganganu barkatai ba tare da wani ilimi ba.
Sun kasu gida uku:
Wasu suka ce su uku ne karensu na huɗu.
Wasu kuma suka ce su biyar ne karensu na shida.
Allah ya ce duk waɗannan maganganu guda biyu shaci-faɗi ne. Sai kuma ya ambaci kashi na uku masu cewa, adadinsu bakwai ne karensu ne na takwas. Sai ya ƙara da umartar Annabi (ﷺ) ya faɗa wa mutane cewa, Ubangijinsu ne mafi sanin adadinsu, waɗanda suka san adadinsu a cikin mutane kaɗan ne. Don haka

jayayya a kan haka ba ta da wani amfani ko maslaha. Saboda haka ya hana Manzonsa ya yi jayayya game da lamarin waɗannan samari, sai fa jayayyar da take bisa hujja da ilimi. Haka kuma ya hana shi neman fatawar wani daga cikin ma'abota littafi a kan sha'anin waɗannan samari.
Allah kuma ya sake yin wani hani ga Annabi (ﷺ) har da sauran al'ummarsa da cewa, kada ya furta zai yi wani abu gobe sai ya ce '*in sha Allah*', sannan idan ya manta ya ambaci Allah; yin haka zai gusar masa da wannan mantuwar ya tuna masa abin da ya manta; ya kuma umarce shi da ya sa ran zai shiryar da shi hanya mafi kusa ga shiriya a kan wannan lamari.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Annabi Sulaiman ɗan Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ce: "Zan kewaya matana su ɗari a wannan dare, kowace ɗaya daga cikinsu za ta haifi yaro wanda zai yi yaƙi don Allah. Sai aka ce masa ya ce '*in sha Allah'*, sai bai faɗa ba. Sai ya kewaya su gaba ɗayansu, to amma babu wadda ta haihu daga cikinsu sai guda ɗaya wadda ita ma rabin mutum ta haifo (watau ɓari ta yi)." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Da a ce ya ce '*in sha Allah*', to da rantsuwarsa ba ta karye ba, da kuma ya cimma buƙatarsa." [Bukhari #2819 da Muslim #1654]

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin lissafi da shekarun *ƙamariyya* da na *shamsiyya*.

2. Idan an tambayi mutum abin da bai sani ba, to ya mayar da iliminsa ga Allah, watau ya ce: Allahu A'alamu, Allah ne mafi sani.

3. Sanin gaibu na sammai da ƙasa yana ga Allah shi kaɗai, babu wanda ya san gaibu sai Allah; shi ne yake sanar da bayinsa abin da ya ga dama su sani.

4. Duk wani mahaluƙi a sammai ko a ƙasa Allah ne mai jiɓintar lamarinsa, shi ne mahaliccinsa mai arzuta shi mai gudanar da al'amarinsa gaba ɗaya. Babu mai yin haka sai shi kaɗai.

5. Babu wanda yake yin tarayya da Allah a cikin hukuncinsa na ƙaddara da na shari'a. Shi kaɗai ne mai halitta, mai gudanar da al'amuran halittunsa; shi kaɗai ne mai tsara dokoki na shari'a da hukunce-hukunce na addini ga bayinsa.

6. Duk Musulmi an umarce shi da ya karanta Alƙur'ani ya yi aiki da shi. Karanta shi kaɗai babu aiki da shi babban tazgaro ne a rayuwar mutum Musulmi.

7. Babu mai ikon ya canza wani hukunci na Allah da ya saukar a littattafansa, kamar yadda babu mai ikon canza wata ƙaddara ta Ubangiji.

8. A wurin Allah kaɗai bawa yake samun mafaka daga duk wani abu da zai cutar da shi.

Suratul Kahf (25-27)
2وَلَبِثُواْ فِي كَهۡفِهِمۡ ثَلَٰثَ مِاْئَةٖ سِنِينَ وَٱزۡدَادُواْ تِسۡعٗا ٢٥ قُلِ ٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا لَبِثُواْۖ لَهُۥ غَيۡبُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ أَبۡصِرۡ بِهِۦ وَأَسۡمِعۡۚ مَا لَهُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَلِيّٖ وَلَا يُشۡرِكُ فِي حُكۡمِهِۦٓ أَحَدٗا ٢٦ وَٱتۡلُ مَآ أُوحِيَ إِلَيۡكَ مِن كِتَابِ رَبِّكَۖ لَا مُبَدِّلَ لِكَلِمَٰتِهِۦ وَلَن تَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلۡتَحَدٗا ٢٧

25. Sun kuwa zauna cikin kogonsu shekara ɗari uku, suka kuma ƙara tara.

26. Ka ce: "Allah ne Mafi sanin tsawon zaman da suka yi." Gaibun da yake sammai da ƙasa nasa ne. Wa ya yi gani irin nasa, wa kuma ya yi ji irin nasa (watau Allah). Ba su da wani majiɓinci in ban da Shi; ba Ya kuma tarayya da wani a cikin hukuncinsa.

27. Kuma ka karanta abin da aka yiwo maka wahayi da shi daga littafin Ubangijinka: Ba mai canja kalmominsa; ba kuma za ka sami wata mafaka ba in ba ta wurinsa ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana adadin shekarun da As'habul Kahfi suka yi suna barci a cikin kogon. Sun zauna a cikinsa tsawon shekara ɗari uku a lissafin shekarar *shamsiyya*, watau lissafi da fitowar rana da faɗuwarta. Amma a lissafin shekarar *ƙamariyya* watau a lissafin ganin wata, sun ƙara shekara tara. Duk shekara ɗari a lissafin *ƙamariyya* tana ƙaruwa da shekara uku ne a kan lissafin *shamsiyya*.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya tabbatar da cewa, Allah ne ya fi kowa sanin yawan shekarun da samarin suka yi a cikin kogon, domin shi ne ya san gaibun sammai da ƙasa, babu wanda ya kai shi gani da ji; yana ganin komai yana kuma jin komai. Shi ne kuma ya ba da labarin lissafin adadin shekarunsu a kogo don haka ba wanda za a ƙara saurara bayan shi. Kuma ban da Allah babu wani mai jiɓintar al'amarinsu, ba ya haɗa wani a cikin hukuncinsa, shi kaɗai ne ɗaya tilo.
Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi aiki da Alƙur'anin a aka saukar masa daga Ubangijinsa sau-da-ƙafa, domin duk bayanan da ya ƙunsa da labarai gaskiya ne, haka kuma hukuncinsa adalci ne. Don haka ya riƙe shi ya yi aiki da shi, babu wani mai canza kalmomin Allah ya kawo wasu a madadinsu, kuma ba zai sami wata mafaka ba in ba daga gare shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar zama tare da mutanen kirki, talakawa ko mawadata, masu ƙarfi ko raunana.

2. Ayar ta ƙunshi masu zama tare don karatun Alƙur'ani.

3. Duk wanda dukiyarsa ko 'ya'yansa ko muƙaminsa ko wani ƙyale-ƙyalen duniya ya shagalar da shi daga ambaton Allah, to zai bi son zuciyarsa ne.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya yi haƙuri da zama tare da Musulmi talakawa da suka yi imani, bai ba shi damar ya kore su daga majalisarsa ba, don kwaɗayin manyan Ƙuraishawa su yi imani, saboda Allah ya san cewa waɗannan kafiran ba imani za su yi ba ko da an biya musu buƙatarsu. Idan ma a ce sun yi imani to a zahiri ne kawai. Sannan kuma korar waɗannan talakawan za ta iya jawo wasu su guji Manzo (ﷺ) su munana masa zato. Watakila wasu sabon-shigar Musulunci ma su yi ridda saboda haka, ba kuma tare da an sami wata babbar nasara ta imanin waɗannan 'yan tsirarun kafiran ba.

5. Musulunci ya zo ne don tabbatar da daidaito a tsakanin 'ya'yansa, babu wanda ya fi wani a wurin Allah sai wanda ya fi tsoron sa.

6. Bayanin cewa, bai dace a bi wani ba a yi masa ɗa'a sai ya kasance mai son Allah da Manzonsa (ﷺ), mai biyayya gare su da yawan ambaton Allah. Malam Ibnul Ƙayyim yana cewa: "Idan bawa ya nufi yin koyi da wani mutum to ya duba ya ga shin yana cikin masu ambaton Allah ko yana cikin gafalallu? Kuma shin yana bin hukuncin son zuciyarsa ne ko wahayi?" [Dubi, Ibnul Ƙayyim, *Al-Wabilus Sayyib*, shafi na 92].

Suratul Kahf (28-29)

وَٱصۡبِرۡ نَفۡسَكَ مَعَ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ رَبَّهُم بِٱلۡغَدَوٰةِ وَٱلۡعَشِيِّ يُرِيدُونَ وَجۡهَهُۥۖ وَلَا تَعۡدُ عَيۡنَاكَ عَنۡهُمۡ تُرِيدُ زِينَةَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَا تُطِعۡ مَنۡ أَغۡفَلۡنَا قَلۡبَهُۥ عَن ذِكۡرِنَا وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ وَكَانَ أَمۡرُهُۥ فُرُطٗا ٢٨ وَقُلِ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكُمۡۖ فَمَن شَآءَ فَلۡيُؤۡمِن وَمَن شَآءَ فَلۡيَكۡفُرۡۚ إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا أَحَاطَ بِهِمۡ سُرَادِقُهَاۚ وَإِن يَسۡتَغِيثُواْ يُغَاثُواْ بِمَآءٖ كَٱلۡمُهۡلِ يَشۡوِي ٱلۡوُجُوهَۚ بِئۡسَ ٱلشَّرَابُ وَسَآءَتۡ مُرۡتَفَقٗا ٢٩

28. Ka kuma haƙurƙurtar da kanka (da zama) tare da waɗanda suke bauta wa Ubangijinsu safe da yamma suna neman yardarsa; kar kuma ka kawar da idanuwanka daga gare su kana neman adon rayuwar duniya; kada kuma ka bi wanda Muka shagaltar da zuciyarsa daga ambatonmu ya kuma bi son ransa, wanda kuma al'amarinsa ya zama a sukurkuce.

29. Kuma ka ce: "Gaskiya daga Ubangijinku take;" to wanda ya ga dama ya yi imani, wanda kuma ya ga dama sai ya kafirta. Lalle kam Mun tanadar wa azzalumai wata wuta wadda katangarta ta kewaye su. Idan kuma suka nemi taimako to za a taimake su ne da ruwa kamar tafasasshen mai da zai riƙa toye fuskoki. Tir da wannan abin shan, makoma kuma ta munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya haƙure wa kansa da zama tare da talakawan sahabbansa waɗanda suke bautar Allah safe da yamma suna masu tsarkake ayyukansu gare shi. Kar ya kuskura idanunsa su ƙetare su su hango wasu waɗanda zai ga dacewar zama tare da su saboda matsayinsu ko wadatarsu.
Malamai sun ce wannan ayar ta sauka ne yayin da manyan Ƙuraishawa suka nemi Manzon Allah (ﷺ) ya kori talakawa cikin sahabbansa daga majalisarsa irin su Bilalu da Ammaru da Suhaibu da Khabbabu da Abdullahi ɗan Mas'udu, idan yana son su musulunta su zauna tare da shi su kaɗai. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana shi korar su, ya kuma umarce shi da ya yi haƙurin zama tare da su.

An karɓo daga Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mun kasance mu shida tare da Manzon Allah (ﷺ) sai mushirikai suka ce: "Ka kori waɗannan kada su riƙa yi mana rashin kunya." A lokacin ni ne da Ibnu Mas'ud da wani mutum ɗan ƙabilar Huzailu da Bilalu da wasu mutane biyu da na manta sunayensu. Sai abin da Allah ya ga dama ya ɗarsu a zuciyar Manzon Allah (ﷺ) ya ɗarsu, wani tunani ya zo masa. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da aya ta 52 a cikin *Suratul An'am*." [Muslim #2413].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana Manzonsa ya yi biyayya ga wanda ya yi watsi da ambaton Allah, wanda har yake umartar Manzo da korar talakawa daga majalisarsa, ya gabatar da bin son zuciyarsa a kan ɗa'ar Ubangijinsa, al'amarinsa kuma duk ya zama a sukurkuce.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya faɗa wa waɗannan gafalallun mutanen masu umartar sa da ya kori Musulmi talakawa, da cewa abin da ya zo musu da shi daga Allah Ubangijinsu shi ne gaskiya, kuma ya jaddada musu cewa, ba zai taɓa korar muminan da suke tare da shi a majalisarsa ba, kamar yadda suke nema a wajensa. Don haka wanda ya ga dama daga cikinsu ya yi imani, zai ga sakamakon imaninsa, wanda kuma ya ga dama ya kafirce, amma ya sani zai ga abin baƙanta rai da yake jiran sa a lahira, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadar wa azzalumai waɗanda suka zaɓi kafirci wuta mai zafin gaske wadda katangarta ta zagaye su ta ko'ina babu wurin gudu. Idan suka nemi a taimaka musu da ruwa saboda tsananin ƙishi sai a taimake su da wani ruwa mai kama da tafasasshen mai wanda zai riƙa toye fuskokinsu don tsananin zafi. Allah ya bayyana cewa, wannan abin sha nasu ya munana, domin ba zai kashe musu ƙishirwa ba kuma ba zai sanyaya musu fatarsu ba. Hakanan wutar da za a saka su a cikinta ta zamanto musu gidan zama ita ma ta munana matuƙa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da Aljanna ne ga mutanen da suka yi imani da shi kuma suka yi ayyuka na ƙwarai.

2. Duk wani aikin alheri da bawa zai yi don Allah, to Allah ba zai tozarta masa shi ba; zai biya shi ladansa cikakke. Don haka ba a raina aikin alheri komai ƙanƙantarsa.

3. ‘Yan Aljanna ana yi musu ado da kayan ado iri-iri, sannan kuma suna rayuwa ta sarakai a cikinta.

Suratul Kahf (30-31)

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ إِنَّا لَا نُضِيعُ أَجۡرَ مَنۡ أَحۡسَنَ عَمَلًا ٣٠ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمُ ٱلۡأَنۡهَٰرُ يُحَلَّوۡنَ فِيهَا مِنۡ أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٖ وَيَلۡبَسُونَ ثِيَابًا خُضۡرٗا مِّن سُندُسٖ وَإِسۡتَبۡرَقٖ مُّتَّكِـِٔينَ فِيهَا عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِۚ نِعۡمَ ٱلثَّوَابُ وَحَسُنَتۡ مُرۡتَفَقٗا ٣١

30. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari tabbas Mu ba ma tozarta ladan wanda ya kyautata aiki.

31. Waɗannan suna da gidajen Aljanna na dawwama waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, ana yi musu ado a cikinsu (watau gidajen) da awarwaro na zinare, suna kuma sanya tufafi koraye na alharini mai shara-shara da mai kauri, suna kwance a kan gadaje. Madalla (da wannan) lada, wurin hutu kuma ya kyautata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake bayyana kyakkyawan tanadin da ya yi wa muminai a lahira, da cewa su ne waɗanda suka yi imani suka yi kyawawan ayyuka. Allah ya tabbatar da cewa, suna da babban rabo, zai kuma cika musu ladansu cib-cib, domin shi ba ya tozarta ladan wanda ya kyautata aikinsa.
Ya bayyana cewa, mutane masu irin waɗannan siffofi a lahira suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su zauna a cikinsu har abada. Za a yi musu ado da awarwaro na zinare, a kuma sanya musu koraye tufafi na alharini mai shara-shara da mai kauri, suna kuma kishingiɗe a cikin gidajen Aljanna a kan wasu karagu waɗanda aka yi musu ado da kyawawan labilaye. Allah ya bayyana cewa, lalle wannan sakamako ya dace da su kuma madalla da shi. Kuma abu ne mai matuƙar kyau a ce gidan Aljanna ya zamo shi ne gidansu na zama har abada.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: ‘‘Adon mumini (a Aljanna) zai kai duk inda alwalarsa ta kai (a jikinsa).’’ [Muslim #250].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar da wannan labarin ba tare da ambaton sunayen waɗannan mutanen biyu ba; domin abin buƙata dai shi ne ɗaukar darasi daga labarinsu, ambaton sunayensu ba ya da wani muhimmanci sosai a nan.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bai wa bayinsa dukiya ne don ya jarrabe su da ita ya ga mai godiya da biyayya gare shi, da wanda zai butulce masa ya yi zalunci da rowa da dukiyar da ya ba shi.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya bai wa kafiri arziƙi mai yawa, ya hana mumini, domin samu da wadatar duniya ba su ne ma'aunin girmamawa a wurin Allah ba, mafi girma a wurinsa shi ne mai kiyaye dokokinsa.

Suratul Kahf (32-36)

*وَٱضۡرِبۡ لَهُم مَّثَلٗا رَّجُلَيۡنِ جَعَلۡنَا لِأَحَدِهِمَا جَنَّتَيۡنِ مِنۡ أَعۡنَٰبٖ وَحَفَفۡنَٰهُمَا بِنَخۡلٖ وَجَعَلۡنَا بَيۡنَهُمَا زَرۡعٗا ٣٢ كِلۡتَا ٱلۡجَنَّتَيۡنِ ءَاتَتۡ أُكُلَهَا وَلَمۡ تَظۡلِم مِّنۡهُ شَيۡـٔٗاۚ وَفَجَّرۡنَا خِلَٰلَهُمَا نَهَرٗا ٣٣ وَكَانَ لَهُۥ ثَمَرٞ فَقَالَ لِصَٰحِبِهِۦ وَهُوَ يُحَاوِرُهُۥٓ أَنَا۠ أَكۡثَرُ مِنكَ مَالٗا وَأَعَزُّ نَفَرٗا ٣٤ وَدَخَلَ جَنَّتَهُۥ وَهُوَ ظَالِمٞ لِّنَفۡسِهِۦ قَالَ مَآ أَظُنُّ أَن تَبِيدَ هَٰذِهِۦٓ أَبَدٗا ٣٥ وَمَآ أَظُنُّ ٱلسَّاعَةَ قَآئِمَةٗ وَلَئِن رُّدِدتُّ إِلَىٰ رَبِّي لَأَجِدَنَّ خَيۡرٗا مِّنۡهَا مُنقَلَبٗا ٣٦

32. Ka kuma ba su misali da wasu mutane su biyu da Muka tanadar wa ɗayansu gonakai biyu na inabi, Muka kuma kewaye su da dabinai, Muka kuma sanya wasu shukoki tsakaninsu.

33. Kowace ɗaya daga gonakin ta ba da 'ya'yanta kuma ba ta rage komai daga gare su ba. Muka kuma ɓuɓɓugo da ƙorama ta tsakiyarsu.

34. Ya zamanto yana da 'ya'yan itace, sai ya ce da abokinsa yayin da yake mahawara da shi: "Ni na fi ka yawan dukiya da ƙarfin jama'a."

35. Ya kuma shiga gonarsa yana kuwa mai zaluntar kansa, ya ce: "Ba na tsammanin cewa wannan za ta ƙare har abada."

36. "Kuma ba na tsammanin alƙiyama za ta tashi, kuma ko da an mayar da ni wurin Ubangijina to lalle zan sami canji fiye ma da ita."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labari na biyu bayan na mutanen kogo. Shi kuma na wasu mutane ne su biyu, su kuma don su zama misali na mutumin da yake godiya ga Allah bisa abin da ya ba shi komai ƙanƙantarsa, da mutumin da zai ba shi ni'ima ta duniya amma ya butulce masa ya kuma kafirce wa ranar alƙiyama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ba wa kafirai misali na wasu mutane su biyu, na farkonsu kafiri ne da Allah ya ba shi wasu gonaki biyu na inabi wanda itaciya ce mai matuƙar daraja, sannan ya kewaye masa waɗannan gonaki da itatuwan dabino waɗanda su ma masu daraja ne sosai. Bayan haka ya sanya masa shuke-shuke a tsakiyarsu na sauran amfanin gona, ya kuma keto masa da wata ƙoramar ruwa ta tsakiyar waɗannan gonaki wadda take shayar da su a noman rani. Duk gonakin nan biyu kuwa suka yi matuƙar kyau, son kowa ƙin wanda ya rasa, kuma suka riƙa bayar da 'ya'yansu da amfaninsu cikakke ba tare da sun rage komai ba. Sai wannan mai gona ya zama yana samun amfanin gona mai matuƙar yawa da kyau, sai duniya ta fara ruɗar sa ya manta da Ubangijinsa, ya ma manta da lahira. Sai wata rana suna mahawara da abokinsa mumini, sai yake nuna masa cewa, shi fa yanzu ba sa'ansa ba ne don ya fi shi yawan dukiya da ƙarfin jama'a masu goyon bayansa da masu yi masa ayyuka da bayi maza da mata da ya mallaka. Sannan bai tsaya da alfaharinsa iya nan ba, sai da ya ƙara da cewa, shi ba ya ma tsammanin akwai tashin alƙiyama; ko ma da a ce za a tashi alƙiyamar shi ya tabbatar yana da makomar da ta fi wannan a wurin Ubangijinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bai dace ba ko kaɗan ga ɗan'adam ya yi wa Allah butulci, alhalin ya san cewa, shi ne mahallicinsa kuma wanda ya kyautata masa halittarsa ya kewaye shi da ni'imominsa.

2. Ni'imar imani da Musulunci ita ce ni'ima ta haƙiƙa, ko da kuwa akwai ƙarancin dukiya da 'ya'ya, domin duk waɗannan masu gushewa ne.

3. Falalar faɗar: "مَا شَاءَ الله لَا قُوَّةَ إِلَّ بِاللَّه ا" a duk yayin da mutum ya ga abin da ya ba shi sha'awa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce mini: "Ya kai Abu Huraira, ba na nuna maka wata taska daga cikin taskokin Aljanna ba da ke ƙarƙashin Al'arshi?" Abu Huraira ya ce: "Sai na ce: E, mahaifina da mahaifiyata fansa ne gare ka." Sai ya ce: "Ka ce: "لَا قُوَّةَ إِلَّ بِاللَّه ا" Watau: Babu wani ƙarfi sai tare da Allah.
Mai ruwaya Abu Baljin ya ce: "Ina tsammanin ya ce: "Lalle Allah zai ce: Bawana ya miƙa wuya ya saduda."
Mai ruwaya Amru ɗan Maimunu ya ce: "Sai na ce wa Abu Huraira: "Ana nufin faɗar:"لَا حَوْلَ وَلَا قُوَّةَ إِلَّا بِاللَّه"?
Sai ya ce: "A'a, ita ce ta cikin Suratul Kahfi:

﴿وَلَوْلَآ إِذْ دَخَلْتَ جَنَّتَكَ قُلْتَ مَا شَآءَ ٱللَّهُ لَا قُوَّةَ إِلَّا بِٱللَّهِ ۚ إِن تَرَنِ أَنَا۠ أَقَلَّ مِنكَ مَالًا وَوَلَدًا﴾

[Ahmad #8426].

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Ba na nuna maka wata taska daga cikin taskokin Aljanna ba? Ita ce faɗar: لَا حَوْلَ وَلَا قُوَّةَ إِلَّا بِاللَّه." [Bukhari #6610 da Muslim #2704].

4. Bayanin cewa, dukiya da 'ya'ya ba za su amfanar da bawa komai ba idan har ba sun taimaka masa ne a kan biyayyar Allah ba.

5. Ya wajaba kada mumini ya karaya a gaban kafiri. Kuma wajibi ne ya yi masa nasiha ya faɗa masa gaskiya, ya jawo hankalinsa zuwa ga imani da Allah da ranar lahira.

Suratul Kahf (37-41)

قَالَ لَهُۥ صَاحِبُهُۥ وَهُوَ يُحَاوِرُهُۥٓ أَكَفَرْتَ بِٱلَّذِى خَلَقَكَ مِن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٍ ثُمَّ سَوَّىٰكَ رَجُلًا ﴿٣٧﴾ لَّٰكِنَّا۠ هُوَ ٱللَّهُ رَبِّى
وَلَآ أُشْرِكُ بِرَبِّىٓ أَحَدًا ﴿٣٨﴾ وَلَوْلَآ إِذْ دَخَلْتَ جَنَّتَكَ قُلْتَ مَا شَآءَ ٱللَّهُ لَا قُوَّةَ إِلَّا بِٱللَّهِ ۚ إِن تَرَنِ أَنَا۠ أَقَلَّ مِنكَ مَالًا وَوَلَدًا ﴿٣٩﴾
فَعَسَىٰ رَبِّىٓ أَن يُؤْتِيَنِ خَيْرًا مِّن جَنَّتِكَ وَيُرْسِلَ عَلَيْهَا حُسْبَانًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فَتُصْبِحَ صَعِيدًا زَلَقًا ﴿٤٠﴾ أَوْ يُصْبِحَ مَآؤُهَا
غَوْرًا فَلَن تَسْتَطِيعَ لَهُۥ طَلَبًا ﴿٤١﴾

37. Abokinsa ya ce da shi yana mai mahawara da shi: "Yanzu ka kafirce wa Wanda Ya halicce ka daga ƙasa, sannan (kuma) daga maniyyi, sannan Ya daidaita ka (ka zama) mutum?

38. "Sai dai ni kam Allah Shi ne Ubangijina, ba kuwa zan haɗa wani da Ubangijina ba.

39. "Kuma mai ya hana ka lokacin da ka shiga gonarka ka ce: 'Abin da Allah Ya ga dama (shi zai kasance). Babu wani ƙarfi kuma babu dabara sai da Allah.' Idan kana gani na na fi ka ƙarancin dukiya da 'ya'ya.

40. “To ina fatan Ubangijina Ya ba ni fiye da gonarka, Ya kuma aiko mata (gonarka) da wani bala’i daga sama, sannan ta wayi gari ta zama ƙeƙasasshiyar ƙasa mai santsi.

41. “Ko kuma ruwanta ya zama ya ƙafe ƙarƙaf, ba ko za ka sami hanyar samo shi ba.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ƙissar mai gonakin nan biyu, da cewa, abokinsa mumini ya yi muhawara da shi yana mai yi masa nasiha yana gargaɗin sa da cewa, yanzu zai kafirce wa Allah wanda ya halicci asalinsa Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga ƙasa, shi kuma ya halicce shi daga maniyyi sannan ya mayar da shi daidaitaccen mutum, ya daidaita masa gaɓoɓinsa har ya zama cikakken mutum; yanzu a ce wanda ya yi masa irin wannan halitta sai ya kasa tashinsa bayan mutuwa?
Sai kuma ya nuna masa bambancinsa da shi, ya tabbatar masa cewa, shi ba zai riƙa maganganu irin nasa ba, shi maganarsa ita ce Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne Ubangijinsa wanda ya yi masa ni’imomi masu yawa, don haka ba zai haɗa wani da shi a wajen bautarsa ba.
Ya ci gaba da jan hankalinsa a kan ya dawo kan hanyar Allah; idan ya shiga gonarsa ya ga irin baiwar da ya yi masa ya ce: “*Ma Sha Allahu La Ƙuwwata Illa Billah*.” Watau ya nuna duk abin da ya faru to Allah ne ya ga damar faruwarsa, kuma shi ba shi da wani ƙarfi ko wata dabara sai tare da Allah.
Sannan ya sanar da shi cewa, ni’imar imani ita ce ni’ima ta gaske ba yawan dukiya ba; don haka ya daina raina shi don ya gan shi ba ya da yawan dukiya da ‘ya’ya. Shi kansa yana sa ran Allah zai ba shi kyautar da ta fi gonar da ya ba shi, shi kuma da ya kafirce wa Allah akwai yiwuwar Allah ya aiko da wata azaba daga sama ta auka wa gonarsa sai ta wayi gari busasshiyar ƙasa da ba wani tsiro kanta; ƙafafu na zamewa saboda santsinta. Ko kuma ruwanta a wayi gari duk ya ƙafe ƙarƙaf, kuma a rasa hanyar samun sa duk kuwa neman da za a sha. Idan kuwa har gona ta rasa ruwa to ta gama lalacewa ke nan.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan Allah ya so bawansa da alheri sai ya gaggauto masa da uƙubar zunubansa tun a nan duniya.

2. Kada duniya da ƙyale-ƙyalenta su rudî bawa har su sanya shi ya manta da Allah mahaliccinsa; ya tuna cewa, duk abin da yake da shi na duniya mai iyaka ne, wata rana zai zo babu shi ya ƙare.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallakar da dukiyar wannan mutumin ba kawai don yana kafiri ba, sai don bugun gaba da amfani da dukiyarsa da ya yi wajen wulaƙanta muminai talakawa, da nunawa a fili cewa, wayonsa ne da dabararsa suka sa ya tara dukiya.

4. Abu ne mai yiwuwa cikin rahamar Allah da falalarsa a ce wannan bawan Allah ya tuba ya kyautata rayuwarsa, domin ya nuna nadamarsa a fili, ya yi da-na-sanin haɗa Allah da wani a cikin bautarsa.

5. Walittaka a wurin Allah ita ce imani da tsoron Allah, kuma tana tabbata ne yayin da sakamako ya bayyana mai kyau, ƙarshe kuma ya yi kyau.

Suratul Kahf (42-44)

وَأُحِيطَ بِثَمَرِهِۦ فَأَصۡبَحَ يُقَلِّبُ كَفَّيۡهِ عَلَىٰ مَآ أَنفَقَ فِيهَا وَهِيَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا وَيَقُولُ يَٰلَيۡتَنِي لَمۡ أُشۡرِكۡ بِرَبِّيٓ أَحَدٗا ٤٢
وَلَمۡ تَكُن لَّهُۥ فِئَةٞ يَنصُرُونَهُۥ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَمَا كَانَ مُنتَصِرًا ٤٣ هُنَالِكَ ٱلۡوَلَٰيَةُ لِلَّهِ ٱلۡحَقِّۚ هُوَ خَيۡرٞ ثَوَابٗا وَخَيۡرٌ عُقۡبٗا ٤٤

42. Aka kuwa hallaka ‘ya’yan itacen nasa, sannan ya wayi gari yana tafa hannayensa kan irin abin da ya ɓatar a kanta, ita kuwa ga ta ta zubo a kan dirkokinta, yana kuma cewa: “Kaicona, ina ma ban haɗa wani da Ubangijina ba!”

43. Ba shi kuwa da wata ƙungiya da za ta taimake shi ban da Allah, kuma bai zamo mai taimaka wa (kansa) ba.

44. A wannan lokacin ne (ya bayyana) cewa taimako na Allah ne Tabbataccen (Sarki). Shi ne Fiyayyen Mai ba da lada kuma Fiyayyen Mai kyautata ƙarshe.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya amsa addu’ar wannan muminin, kuma abin da yake tsammani shi ne ya tabbata, sai ko bala’i ya rutsa da gonakin wannan mutum, duk abin da ke cikinsu ya lalace. Ya wayi gari cikin nadama, yana tafa hannayensa kan yawan dukiyar da ya kashe a waɗannan gonaki nasa da wahalhalun da ya sha wajen lura da su, ga su yau kwance a ƙasa, yana cewa cikin nadama: Ina ma ya yi imani da Allah shi kaɗai bai haɗa kowa da shi ba!
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa,, duk wani abu da mutumin nan yake alfahari da shi a baya yau bai amfane shi da komai ba, ƙarfin jama’arsa bai taimaka masa da wani abu ba ya kare masa bala’in da ya auka masa; shi ma kuma bai iya tsinana wa kansa komai ba.
A wannan lokaci ne da Allah ya hallakar da wanda ya kafirce masa ya fifita rayuwar duniya a kan ta lahira, ya kuma bayyana darajar wanda yake masa godiya da babban matsayinsa a wurinsa; a lokacin ne ya tabbata lalle taimako na ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tabbataccen Sarki shi kaɗai, shi ne fiyayyen mai saka wa bayinsa muminai, ya kuma ruɓanya musu ladansu, kuma fiyayyen mai kyautata ƙarshensu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin yadda rayuwar duniya take da saurin shuɗewarta idan an kwatanta ta da rayuwar lahira ta har abada, don haka bai dace ba mai hankali ya shagaltar da rayuwarsa wajen gina duniya ya mance da ranar lahira.

2. Ayyukan ƙwarai wanzazzu sun ƙunshi duk wasu ayyukan ɗa’a ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) na wajibi da na mustahabbi; na haƙƙoƙin Allah da na bayinsa, irin su salla da zakka da sadaƙa da hajji da umara da zikiri da neman ilimi mai amfani da wa’azi da sada zumunci da kula da haƙƙoƙin iyali da na dabbobi da duk wani kyakkyawan aiki na kyautatawa ga al’umma. Duk waɗannan suna cikin ayyuka nagari wanzazzu.

Suratul Kahf (45-46)

وَٱضۡرِبۡ لَهُم مَّثَلَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا كَمَآءٍ أَنزَلۡنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخۡتَلَطَ بِهِۦ نَبَاتُ ٱلۡأَرۡضِ فَأَصۡبَحَ هَشِيمٗا تَذۡرُوهُ ٱلرِّيَٰحُۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ مُّقۡتَدِرًا ٤٥ ٱلۡمَالُ وَٱلۡبَنُونَ زِينَةُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَٱلۡبَٰقِيَٰتُ ٱلصَّٰلِحَٰتُ خَيۡرٌ عِندَ رَبِّكَ ثَوَابٗا وَخَيۡرٌ أَمَلٗا ٤٦

45. Kuma ka ba su misalin rayuwar duniya (wadda take) kamar ruwa ne da Muka saukar da shi daga sama, sai tsirran ƙasa suka cakuɗa da shi, sannan ya zama busasshe, iska tana ɗaidaita shi. Allah kuwa Ya kasance Mai iko ne a kan komai.

46. Dukiya da ‘ya’ya adon rayuwar duniya ne; wanzazzun ayyuka nagari kuwa su suka fi lada a wurin Ubangijinka kuma su ne buri mafi alheri.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa wa masu ruɗuwa da duniya yadda misalinta yake wajen saurin gushewa da ƙarewa, kamar ruwan sama ne da Allah ya saukar da shi ƙasa, tsirran ƙasa suka gauraya da shi suka fito suka yi kyau abin ban sha'awa, amma sai daga ƙarshe su bushe su kakkarye su zama karmami iska tana ɗaukar su har su watse, ƙasa ta koma kamar yadda take tun farko. Allah ya tabbata mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi, yana raya abin da ya ga dama ya hallaka abin da ya ga dama.
Sai kuma ya bayyana cewa, dukiya da 'ya'ya ƙawa ce ta duniya. Dukiya ba za ta amfanar da komai a lahira ba sai abin da mutum ya ciyar na dukiyarsa don neman yardar Allah. Ya kuma tabbatar da cewa, ayyuka da maganganu na ƙwarai su suka fi lada a wurin Ubangiji fiye da duk abin da duniya ta ƙunsa na dukiya da ƙawarta, kuma su ne mafi alherin abin da mutum zai yi burin sa a lahira, domin ƙyale-ƙyalen duniya masu ƙarewa ne, amma ayyuka na ƙwarai wanzazzu ne har abada.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Faɗar: *Subahanallahi Wal-Hamdu Lillahi Wa La-Ilaha Illallahu Wal-Lahu Akbar* suna daga cikin wanzazzun ayyuka nagari." [Ibnu Jarir, *Jami'ul Bayan*, Juzu'i na 18, shafi na 34].

An tambayi Usman (Allah ya ƙara masa yarda) cewa,: Mene ne wanzazzun ayyuka? Sai ya ce: "Su ne faɗar: *La Ilaha Illallahu Wa Subhanallahi Wal-Hamdu Lillahi Wallahu Akbar Wa La Haula Wala Ƙuwwata Illa billahi*." [Ahmad #513].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A ranar alƙiyama Allah zai tashi kowa da komai, babu abin da za a bari mai rai ba a tashe shi ba domin yin hisabi.

2. A ranar alƙiyama Allah zai tattara halittu sahu-sahu, duk masu aiki iri ɗaya a tattara su a sahunsu daban.

3. Yadda kowa ya zo duniya shi kaɗai ba dukiya ba iyali ba komai babu dangi, to haka zai koma ga Allah babu komai tare da shi sai ayyukansa da ya yi a duniya.

4. Littafin ayyukan bawa zai tattara duk wani aiki na mutum babba da ƙarami. Wajibi ne mutum ya guji ayyukan laifi komai ƙanƙantarsu domin za su tattaru wuri guda su yi yawa, kuma ya yawaita neman gafarar Allah domin ya rage zunuban da suke cikin littafinsa na ayyuka.

5. Tabbatar da karkasuwar zunubai zuwa manya da ƙanana, kuma dukkansu za a rubuta su a littafin bawa.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya zalunci, domin shi cikakken adali ne, don haka ne ya bayyana wa bayinsa abin da ya yarda su yi da wanda bai yarda su aikata ba, domin ya kama mai laifi da laifinsa bayan tsayuwar hujja a kansa.

Suratul Kahf (47-49)

وَيَوۡمَ نُسَيِّرُ ٱلۡجِبَالَ وَتَرَى ٱلۡأَرۡضَ بَارِزَةٗ وَحَشَرۡنَٰهُمۡ فَلَمۡ نُغَادِرۡ مِنۡهُمۡ أَحَدٗا ٤٧ وَعُرِضُواْ عَلَىٰ رَبِّكَ صَفّٗا لَّقَدۡ جِئۡتُمُونَا كَمَا
خَلَقۡنَٰكُمۡ أَوَّلَ مَرَّةِۭۚ بَلۡ زَعَمۡتُمۡ أَلَّن نَّجۡعَلَ لَكُم مَّوۡعِدٗا ٤٨ وَوُضِعَ ٱلۡكِتَٰبُ فَتَرَى ٱلۡمُجۡرِمِينَ مُشۡفِقِينَ مِمَّا فِيهِ

وَيَقُولُونَ يَٰوَيۡلَتَنَا مَالِ هَٰذَا ٱلۡكِتَٰبِ لَا يُغَادِرُ صَغِيرَةٗ وَلَا كَبِيرَةً إِلَّآ أَحۡصَىٰهَاۚ وَوَجَدُواْ مَا عَمِلُواْ حَاضِرٗاۗ وَلَا يَظۡلِمُ رَبُّكَ أَحَدٗا٤٩

47. Kuma ka tuna ranar da za Mu tafiyar da duwatsu kuma ka ga ƙasa a baje (ba tudu ba rafi), Mu kuma tattara su (gaba ɗaya), ba Mu bar ɗaya daga cikinsu ba.

48. Aka kuma kawo su a gaban Ubangijinka sahu-sahu (a ce da su): "Haƙiƙa kun zo mana kamar yadda tun farko Muka halicce ku. Ba ma haka ba, kun riya cewa ba za Mu sanya muku wani wa'adi ba."

49. Aka kuma ajiye littafin (ayyukansu), sannan sai ka ga masu laifi suna cike da tsoron abin da yake cikinsa, suna kuma cewa: "Kaiconmu, me ya sami wannan littafin, ba ya barin (aiki) ƙarami balle babba sai ya ƙididdige su. Suka kuma sami (duk) abubuwan da suka aikata an zo da su. Ubangijinka kuwa ba zai zalunci kowa ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tuna da ranar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai gusar da duwatsu daga wuraren zamansu ya zamanto ƙasa ta fito fili domin an kawar da duk wasu duwatsu da bishiyoyi da gine-gine da suke bayanta. Allah kuma ya tattara halittu wuri guda ba tare da ya bar ko mutum ɗaya ba sai ya tashe shi.
Ya bayyana cewa, zai tara ɗaukacin mutane a gaban Ubangiji sahu-sahu domin yi musu hisabi. Sai Ubangiji ya ce da su, ga shi yanzu sun zo masa ɗai-ɗai, kowa a tsirara haihuwar uwarsa, ba takalma a ƙafafunsu kuma ba su da shayi, kamar dai yadda tun farko ya halicce su, bayan a da suna riya cewa, ba za a sake tashin su ba idan sun mutu, kuma babu wani wuri da aka tanada don komawarsu inda za a yi musu hisabi a yi wa kowa sakamako a kan ayyukansa.

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Za a tashi mutane a ranar alƙiyama babu takalma a ƙafafunsu tsirara masu loɓa." Sai A'isha ta ce: "Ya Manzon Allah, duk za a haɗa maza da mata wuri guda suna kallon junansu?" Sai ya ce: "Ya A'isha, abin ya fi ƙarfin su tsaya kallon junansu." [Bukhari #652 da Muslim #2159].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya ku mutane, lalle za a tattara ku a gaban Allah tsirararku masu loɓa, (kamar yadda muka fara halitta haka za mu mayar da ita). Ku saurara, farkon wanda za a saka wa tufafi a ranar alƙiyama shi ne Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi)..." [Bukhari #2526 da Muslim #2860].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, za a ajiye littafin ayyuka; wani a ba shi littafinsa a hannun dama, wani a ba shi nasa a hannun hagu. A nan ne za a ga kafirai suna cike da tsoron abin da yake cikin littattafansu, domin sun riga sun san ta'asar da suka aikata a duniya ta kafirci da saɓon Allah. A lokacin ne za su riƙa ihu suna cewa, sun banu sun hallaka, suna mamakin irin wannan littafin da ba zai bar ƙaramin abu da babba na ayyukan da suka yi a duniya ba face sai ya kiyaye su a rubuce. Suka kuwa samu abubuwan da suka aikata a duniya an halarto musu su gaba ɗaya, kuma Allah ba azzalumin kowa ba ne; ba zai kama wani da laifin wani ba, ko ya rage wa wani ladan aikinsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Unaisu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Za a tashi mutane a ranar alƙiyama tsirara masu loɓa babu komai tare da su. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo su da wata murya wadda na nesa yake jin ta kamar yadda na kusa yake ji, ya ce: "Ni ne cikakken Sarki, ni ne mai sakamako, bai dace wani ɗan wuta ya shiga wuta ba alhali akwai haƙƙinsa a wurin wani ɗan Aljanna har sai na rama masa, kuma bai dace wani ɗan Aljanna ya shiga Aljanna ba alhalin akwai

haƙƙinsa a wurin wani ɗan wuta har sai na karɓo masa, ko na rama masa ko da kuwa mari ne.'' Sai sahabbai suka ce: ''Ta yaya za a karɓo wannan haƙƙi alhali dukkanmu za mu tashi ba mu da komai?'' Sai Annabi (ﷺ) ya ce: ''Da kyawawan ayyuka da munana.'' [Ahmad #16042].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mala'iku sun yi wa Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sujjada domin biyayya ga umarnin Allah. Don haka bai dace wani ya yi wa wani sujjada ba saboda Shari'a ta yi hani a kan haka.

2. Asalin Iblis daga jinsin aljannu yake, kuma shi ne ubansu, kamar yadda Annabi Adamu yake uban mutane.

3. Iblis yana da zurriyya. Imamu As-Sha'abi ya ce: ''Wani mutum ya tambaye ni cewa, shin Iblis yana da mata?'' Sai na ce masa: ''Wannan aure ne da ban halarce shi ba.'' Sai kuma na tuna faɗar Allah: ''Yanzu kwa riƙe shi da zurriyyarsa masoya ba ni ba?'' Sai na gane cewa, ba a samun zurriyya sai da mata, sai na ce masa: ''E.'' [Dubi, *Alƙurɗubi*, Juzu'i na 5, shafi na 634-635].

Malam Ƙatada ya ce: ''Suna hayayyafa kamar yadda 'yan'adam suke hayayyafa, amma sun fi 'yan'adam yawa.'' [Abu As-Shaikh, Al-Azamah, Juzu'i na 5, shafi na 1685].

4. Umarni da kwaɗaitarwa a kan ɗaukan Shaiɗan a matsayin maƙiyi.

5. Babu mai mayar da Shaiɗan masoyi sai azzalumi.

6. Ba ya kamata ga muminai su nemi taimakon azzalumai ɓatattu masu ɓatarwa, domin ba za su amfane su da komai ba sai dai ma su cutar da su.

7. Duk wanda ya riƙe wani a duniya yana bautar sa ba Allah ba, to ba zai amfana masa komai ba a lahira, makomarsa da shi da abin bautarsa wutar Jahannama ce.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai nuna wa kafirai wuta tun kafin a jefa su cikinta.

Suratul Kahf (50-53)

وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُواْ لِأَدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبْلِيسَ كَانَ مِنَ ٱلْجِنِّ فَفَسَقَ عَنْ أَمْرِ رَبِّهِۦٓ ۗ أَفَتَتَّخِذُونَهُۥ وَذُرِّيَّتَهُۥٓ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِى وَهُمْ لَكُمْ عَدُوٌّ ۚ بِئْسَ لِلظَّٰلِمِينَ بَدَلًا ﴿٥٠﴾ ۞ مَّآ أَشْهَدتُّهُمْ خَلْقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلَا خَلْقَ أَنفُسِهِمْ وَمَا كُنتُ مُتَّخِذَ ٱلْمُضِلِّينَ عَضُدًا ﴿٥١﴾ وَيَوْمَ يَقُولُ نَادُواْ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُمْ فَدَعَوْهُمْ فَلَمْ يَسْتَجِيبُواْ لَهُمْ وَجَعَلْنَا بَيْنَهُم مَّوْبِقًا ﴿٥٢﴾ وَرَءَا ٱلْمُجْرِمُونَ ٱلنَّارَ فَظَنُّوٓاْ أَنَّهُم مُّوَاقِعُوهَا وَلَمْ يَجِدُواْ عَنْهَا مَصْرِفًا ﴿٥٣﴾

50. Kuma ka tuna lokacin da Muka ce da mala'iku: ''Ku yi sujjada ga Adamu'', sai suka yi sujjadar in ban da Iblis, ya kasance kuwa daga cikin aljannu, sai ya saɓa wa umarnin Ubangijinsa. Yanzu kwa riƙe shi shi da zurriyarsa masoya ba Ni ba, alhali kuwa su maƙiyanku ne? Wannan canji na azzalumai ya munana.

51. Ban halarto da su ba lokacin halittar sammai da ƙasa, ko ma halittar kawunansu, ban kuma kasance Mai rikon masu ɓatarwa mataimaka ba.

52. Kuma (ka tuna) ranar da (Allah) zai ce (da kafirai): “Ku kirawo abokan tarayyar nawa waɗanda kuka riya (cewa su ne iyayen gijinku)”, to sai suka kirawo su, sai ba su amsa musu ba, Muka kuma sanya mahallaka a tsakaninsu.

53. Masu laifi kuma suka ga wuta sai suka tabbatar da cewa lalle za su shige ta ba kuwa za su sami wata makauta ba daga gare ta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin asalin farkon halittar ɗan’adam, yayin da ya halicci Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kuma umarci mala’iku da su yi masa sujjada ta girmamawa da gaisuwa, sai dukkansu suka faɗi suka yi masa sujjada domin cika umarnin Ubangijinsu. To amma shi Iblis sai ya ƙi ya yi biyayya ga wannan umarni na mahaliccinsa. Kuma da ma shi ba mala’ika ne ba, ya kasance ne daga cikin jinsin aljannu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da zurriyyarsa cewa, yanzu sa yarda su ɗauki Iblis da zurriyyarsa su zama masoya da za su jiɓince su ba Allah ba, alhalin ga shi ya tabbata shi maƙiyansu ne? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wadarai da azzalumai waɗanda za su saki Allah su riƙe Iblis da zurriyyarsa masoya.

An karɓo daga Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle Iblis yana ajiye karagarsa a kan ruwa, sannan ya baza rundunarsa, wanda ya fi kusanci da matsayi a wurinsa shi ne wanda ya fi fitina daga cikinsu. Ɗaya daga cikinsu zai zo ya ce, na yi kaza da kaza, sai Iblis ya ce: “Tafi can ba ka yi komai ba.” Sai wani kuma ya zo ya ce: “Ban ƙyale shi ba har sai da na raba shi da matarsa.” Sai ya matso da shi kusa da shi ya ce: “Madalla da kai.” Ya kama shi ya rungume shi.” [Muslim #2813].

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash’ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Duk sanda garin Allah ya waye Iblis yana baza rundunarsa yana ce musu: “Duk wanda ya ɓatar da wani Musulmi to zan naɗa masa kambin sarauta.” Sai wani ya fita ya dawo ya ce: “Ban ƙyale shi ba har sai da na ga ya saki matarsa.” Sai Iblis ya ce: “Ba jimawa zai sake wani auren.” Sai kuma ya zo ya ce: “Ban ƙyale shi ba har sai da na ga ya ɓata da iyayensa.” Sai Iblis ya ce: “Ai ba da jimawa ba zai dawo ya sasanta da su, ya ci gaba da yi musu biyayya.” Sai kuma wani ya zo ya ce: “Ban ƙyale shi ba har sai da na ga ya yi zina.” Sai Iblis ya ce: “Babu kamarka.” Wani kuma sai ya zo ya ce: “Ban ƙyale shi ba har sai da na ga ya kashe rai.” Sai Iblis ya ce: “Babu kamarka.” Sai ya naɗa masa kambin sarautarsa.” [Ibn Hibban #6186 da *Mustadrak* na Hakim, Juzu’i na 4, shafi na 350].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan da suka runguma suna bautar su ba Allah ba su ma bayi ne kamarsu, ba su da wani matsayi na daban a wurin Allah, domin bai zo da su ba ya nuna musu lokacin da yake halittar sammai da ƙasa, hakanan bai zo da su ya nuna wa wani sashinsu sanda ya halicci wani sashe ba. Shi kaɗai ne mai halitta, kuma mai gudanar da abin da ya halitta, kuma bai zamo mai riƙon masu ɓatarwa daga cikin shaiɗanu na mutane ko aljanu su zama mataimakansa ba, domin shi wadatacce ne da Zatinsa ba ya buƙatar taimakon kowa.
Sai kuma ya bayyana yadda zai nuna wa masu bautar wasu ba shi ba cewa, ƙarya suke bauta wa ba gaskiya ba. Ya umarci Annabinsa ya tuna ranar alƙiyama sa’adda zai umarci waɗanda suka yi shirka a nan duniya da su kirawo waɗanda suka riƙa da’awar cewa, su ababen tarayya ne na Allah, su kirawo su su ga ko za su taimaka musu da wani abu a wannan ranar. Sai su kirawo su amma ba za su ji sun amsa musu ba ballantana su taimaka musu. Allah ya bayyana cewa, zai sanya wurin hallaka, watau wutar Jahannama, a tsakaninsu, a nan ne za su yi baran-baran da junansu.

Sai kuma ya bayyana cewa, bayan an yi hisabi kowa ya san makomarsa, azabar Allah ta wuta ta tabbata ga masu laifi, to a lokacin za su gan ta an zo da ita, su kuma tabbatar da cewa, cikinta za a jefa su, ba kuma za su samu wurin kauce mata ba, dole ne sai sun shige ta ba makawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani cike yake da misalai iri-iri don tabbatar da abubuwa daban-daban:
• Wani lokaci don tabbatar da tashin alƙiyama.
• Wani lokaci kuma don tabbatar da Kaɗaitakar Allah.
• Wani lokaci kuma don bayanin halin duniya yadda take.
• A wani lokaci kuma domin bayanin yadda lahira take.
• A wasu lokuta a tsawaita misalin, a wasu lokuta kuma a taƙaita su.

2. Duk wata jayayya don dakushe gaskiya ko ture ta, jayayya ce abar suka a wurin Allah.

3. Ba rashin bayyanar hujja ko rashin ƙarfinta ne ya hana kafirai karɓar Musulunci ba; taurin kai ne kawai da rashin rabo a wurin Allah.

4. Bushara da gargaɗi su ne manyan ayyukan manzannin Allah.

5. Izgili da hukunce-hukuncen Shari'a izgili ne da ayoyin Allah.

Suratul Kahf (54-56)

وَلَقَدۡ صَرَّفۡنَا فِي هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ لِلنَّاسِ مِن كُلِّ مَثَلٖۚ وَكَانَ ٱلۡإِنسَٰنُ أَكۡثَرَ شَيۡءٖ جَدَلٗا ٥٤ وَمَا مَنَعَ ٱلنَّاسَ أَن يُؤۡمِنُوٓاْ إِذۡ جَآءَهُمُ ٱلۡهُدَىٰ وَيَسۡتَغۡفِرُواْ رَبَّهُمۡ إِلَّآ أَن تَأۡتِيَهُمۡ سُنَّةُ ٱلۡأَوَّلِينَ أَوۡ يَأۡتِيَهُمُ ٱلۡعَذَابُ قُبُلٗا ٥٥ وَمَا نُرۡسِلُ ٱلۡمُرۡسَلِينَ إِلَّا مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَۚ وَيُجَٰدِلُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِٱلۡبَٰطِلِ لِيُدۡحِضُواْ بِهِ ٱلۡحَقَّ وَٱتَّخَذُوٓاْ ءَايَٰتِي وَمَآ أُنذِرُواْ هُزُوٗا ٥٦

54. Kuma haƙiƙa Mun sassarafa kowane irin misali ga mutane a cikin wannan Alƙur'anin. Mutum kuwa ya kasance wanda ya fi komai yawan musu.

55. Ba kuwa abin da ya hana mutane su yi imani lokacin da shiriya ta zo musu, su kuma nemi gafarar Ubangijinsu har sai irin abin da ya zo wa mutanen farko ya zo musu, ko kuwa azaba ta zo musu gaba-da-gaba.

56. Ba Mu kuma aiko da manzanni ba sai don su zama masu albishir mai gargaɗi. Su kuma waɗanda suka kafirce sai su dinga jayayya da ƙarya don su kawar da gaskiya da ita; suka kuma riƙi ayoyina da kuma abin da aka yi musu gargaɗi da shi a matsayin abin izgili.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa,, ya yi bayanin misalai iri-iri a cikin Alƙur'ani domin mutane su wa'azantu su hankalta, sai dai mutum, musamman kafiri yana da yawan jayayya a kan gaskiyarsa (Alƙur'ani) da take a bayyane ƙarara.

An karɓo daga Abu Umamata (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu mutanen da za su bar shiriyar da suka kasance a kanta sai an hore musu jayayya." [Ahmad #22164 da Tirmizi #3253 da Ibn Majah #48].

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Mun kasance muna zaune tare da Manzon Allah (ﷺ) sai ya yi dariya, sai ya ce: "Ko kun san dalilin dariyata?" Sai muka ce: "Allah da Manzonsa su ne mafi sani." Sai ya ce: "Ina dariya ne a kan yadda bawa zai riƙa magana da Ubangijinsa (ranar alƙiyama), ya ce: "Ya Ubangijina, shin ba ka tsare ni daga zalunci ba?" Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: "E, haka ne." Sai bawa ya ce: "To ban yarda wani ya ba da shaida a kaina ba sai dai wata gaɓa ɗaya daga jikina." Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: "To kai ma a yau ka isa shaida ga kanka, hakanan su ma mala'iku masu girma marubuta ayyuka sun isa shaidu." Sai a rufe masa bakinsa, sannan a ce wa gaɓoɓinsa su yi masa shaida. Sai gaɓoɓinsa su yi bayanin duk ayyukan da ya yi (a duniya), sai a kuma ba shi damar ya yi magana, sai ya ce: "Tir da ku, a kanku ne fa nake wannan jayayyar." [Muslim #2969].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba rashin bayani cikakke ne ya hana kafirai su yi imani da abin da Annabi (ﷺ) ya zo musu da shi daga Allah ba, ko su nemi gafarar zunubansu daga Allah. An yi musu bayani filla-filla tare da ba su misalai iri-iri a cikin Alƙur'ani da kawo musu hujjoji masu ƙarfi. Abin da kawai ya hana su ba da gaskiya shi ne irin gangancin da suke yi na neman cewa su ma a saukar musu da azaba irin wadda aka saukar wa al'ummun da suka gabace su, idan har abin da Manzo ya zo musu da shi gaskiya ne. Ko kuma su ga azabar da ake tsoratar da su da ita ido-da-ido, a lokacin ne za su yarda abin da Manzo ya zo musu da shi gaskiya ne.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, ba wasu manzanni da ya aiko sai don su yi albishir ga muminai masu bin Allah da Manzonsa, su kuma yi gargaɗi ga kafirai da masu saɓon Allah. Ba su da ikon tursasa wa mutane sai sun yi imani. Amma duk da haka kafirai suna jayayya da manzannin Allah tare da cewa sai sun nuna musu dalilai a fili, ba don wani abu ba sai don su kawar da gaskiyar da aka saukar wa Manzon Allah (ﷺ) ta hanyar ƙarerayinsu. Kuma suka ɗauki Alƙur'ani da azabar Allah da ake tsoratar da su abin yi wa izgili da dariya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haɗarin bijire wa wa'azi da faɗakarwar masu faɗakarwa.

2. Wanda ya kafe a kan ɓata bayan duk bayanai sun zo masa, Allah yakan rufe masa zuciya, ba zai taɓa gane gaskiya ba bayan haka, sannan ya toshe masa jinsa ba zai taɓa sauraron gaskiya ya dawo ba, sakamakon bijirewarsa da kafewarsa a kan ɓata.

3. Allah mai yawan gafara ne da karɓar tubar duk wanda ya tuba daga kowane irin laifi ne, domin rahamarsa ta yalwaci komai da kowa.

4. Allah mai haƙuri ne, ba ya gaggauto wa da masu laifi azaba, domin ya ba su damar tuba da komawa gare shi.5. Girman hadarin zalunci kowane iri ne.

Suratul Kahf (57-59)

وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِاٰيَٰتِ رَبِّهِۦ فَأَعْرَضَ عَنْهَا وَنَسِىَ مَا قَدَّمَتْ يَدَاهُ ۚ إِنَّا جَعَلْنَا عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ أَكِنَّةً أَن يَفْقَهُوهُ وَفِىٓ ءَاذَانِهِمْ وَقْرًا ۖ وَإِن تَدْعُهُمْ إِلَى ٱلْهُدَىٰ فَلَن يَهْتَدُوٓا۟ إِذًا أَبَدًا ﴿٥٧﴾ وَرَبُّكَ ٱلْغَفُورُ ذُو ٱلرَّحْمَةِ ۖ لَوْ يُؤَاخِذُهُم بِمَا كَسَبُوا۟ لَعَجَّلَ لَهُمُ ٱلْعَذَابَ ۚ بَل لَّهُم مَّوْعِدٌ لَّن يَجِدُوا۟ مِن دُونِهِۦ مَوْئِلًا ﴿٥٨﴾ وَتِلْكَ ٱلْقُرَىٰٓ أَهْلَكْنَٰهُمْ لَمَّا ظَلَمُوا۟ وَجَعَلْنَا لِمَهْلِكِهِم مَّوْعِدًا ﴿٥٩﴾

57. Wane ne ya fi zalunci fiye da wanda aka yi masa gargaɗi da ayoyin Ubangijinsa sannan ya bijire musu, ya kuma manta abin da hannayensa suka gabatar (na mugun aiki). Lalle Mun sanya rufi a zukatansu don kada su fahimce shi (Alƙur'ani), a cikin kunnuwansu kuma (Muka sanya) wani nauyi. Idan kuwa ka kirawo su zuwa ga shiriya to ba za su yi imani ba har abada.

58. Ubangijinka kuwa Mai yawan gafara ne Ma'abocin rahama; da Yana kama su da abin da suka aikata, to da Ya gaggauta musu azaba. A'a, (ba Ya yin haka), sai dai suna da ƙayyadajjen lokaci wanda ba za su sami wata makauta ba daga gare shi.

59. Kuma waɗancan alƙaryu Mun hallakar da su yayin da suka yi zalunci, Muka kuma sanya ƙayyadajjen lokaci na hallakar da su.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu azzalumi da ya kai mutumin da aka riƙa yi masa wa'azi da ayoyin Allah amma ya yi ko-oho da su, bai damu da abin da ake tsoratar da shi ba na azabar Allah, ya riƙa bijire wa gaskiya duk sanda ya ji ta, ya ma manta da ayyukan kafirci da saɓon Allah da ya riƙa yi a duniya bai tuba ba ya yi nadama a kansu ba. Lalle duk inda wani azzalumi ya kai wannan ya wuce nan.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da yake faruwa ga mutane masu irin wannan hali, da cewa, Allah ya rufe zukatansu ruf sun kasa fahimtar Alƙur'ani, ya mayar da kunnuwansu kurame ba za su saurari Alƙur'ani sauraro na karɓa ba, don haka ko da za a kirawo su zuwa su yi imani ba za su taɓa amsa kiran ba har abada domin zukatansu a rufe suke, kunnuwansu kuma sun kurumce.
To don gudun kada Manzon Allah (ﷺ) ya zaci cewa waɗannan kafirai tun da har sun kai ga irin wannan matsayi na bijire wa Allah ba zai ƙyale su haka a duniya ba tare da ya saukar musu da azaba ta hallaka su ba, Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa, ba haka abin zai kasance ba. Shi Allah mai yawan gafarta zunubban bayinsa ne masu tuba, kuma mai rahama ne wanda rahamarsa ta yalwaci komai. Yana kuma daga cikin rahamarsa ya saurara wa masu laifi ko sa tuba ya karɓi tubansu. Ya bayyana cewa, da a ce zai kama waɗannan masu laifin da azabarsa, to da ya gaggauto musu da ita tun a nan duniya, to amma shi mai haƙuri ne, don haka ya bar su domin su tuba. Ya bayyana cewa, akwai lokaci da wuri da ya tanada inda zai yi musu sakayya a kan kafircinsu da zunubansu idan ba su tuba ba, kuma ba za su taɓa samun mafaka da za ta kare su daga gare shi ba.
Sai kuma ya bayyana cewa, haka al'adar Allah ta kasance a cikin al'ummun da suka gabata; yana saurara musu yayin da suka yi kafirci don su tuba su koma gare shi. Idan sun doge a kan kafircinsu sai ya aiko musu da azabarsa idan wa'adin hallaka su ya yi, babu kuma wanda ya isa ya kauce wa wannan wa'adin nasa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin fita neman ilimi ko da kuwa tafiya ce mai nisa.

2. Sanar da abokin tafiya maƙasudin yinta da kuma nisanta, domin ya yi mata tanadin da ya dace.

3. Ɗaukar guzuri yayin tafiya don kauce wa roƙon mutane abin hannunsu.

4. Halaccin tafiya da mai hidima idan akwai buƙatar haka.

5. Annabawa kamar sauran mutane su ma sukan yi mantuwa.

Suratul Kahf (60-61)

وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِفَتَىٰهُ لَآ أَبْرَحُ حَتَّىٰٓ أَبْلُغَ مَجْمَعَ ٱلْبَحْرَيْنِ أَوْ أَمْضِىَ حُقُبًا ﴿٦٠﴾ فَلَمَّا بَلَغَا مَجْمَعَ بَيْنِهِمَا نَسِيَا حُوتَهُمَا فَٱتَّخَذَ سَبِيلَهُۥ فِى ٱلْبَحْرِ سَرَبًا ﴿٦١﴾

60. Kuma (ka tuna) lokacin da Musa ya ce da yaronsa: "Ba zan dakata da (tafiyata) ba har sai na kai mahaɗar kogunan nan biyu, ko kuwa in zarce har tsawon shekaru."

61. To lokacin da suka isa mahaɗar tasu (watau kogunan) sai suka manta da kifinsu wanda ya kama hanyarsa a cikin kogi kamar ɗakin ƙarƙashin ƙasa.

Daga nan har zuwa ƙarshen aya ta 82 Allah ya ba da labarin tafiyar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) neman ilimi wajen Annabi Khadir (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Labarin wannan tafiyar ya zo a cikin hadisin Ubayyu ɗan Ka'ab wanda [Bukhari #122, 2728, 3400, 3401, 4725, 4726, 2727, 6072, 7477 da Muslim #2380] suka ruwaito cewa, wata rana Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tashi a cikin Banu Isra'ila ya yi musu huɗuba ya yi musu wa'azi har mutane suka yi ta yin kuka. Bayan ya gama ya tafi, sai wani mutum ya bi shi ya tambaye shi cewa, wane mutum ne ya fi kowa ilimi? Sai ya ce shi ne ya fi kowa ilimi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɓe shi a kan hakan, domin kamata ya yi ya mayar da ilimi gare shi shi kaɗai. Sai ya yi masa wahayi da cewa, akwai wani bawansa a wata mahaɗar koguna biyu shi ya fi shi ilimi. Sai Annabi Musa ya tambayi Allah ya faɗa masa yadda zai isa inda yake. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya tanadi guzurin kifi tare da shi ya saka shi a cikin kwando, to duk inda ya ga kifin nan ya ɓace to a nan ne wannan bawan Allah yake.
Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sami mataccen kifi ya sanya a kwando kamar yadda aka umarce shi, ya ɗauki yaronsa mai suna Yusha'u suka tafi, ya gaya masa cewa, ba zai daina tafiya ba har sai ya kai wurin da kogunan nan suka haɗu, ko da kuwa wannan tafiyar za ta ɗauke shi shekaru masu yawa.
Wannan mahaɗar kogunan malamai sun yi saɓani wajen tantance ta. Wasu sun ce ita ce mahaɗar kogunan Farisa da Rum; wasu sun ce a Sham take; wasu kuma sun ce a Afrika ce. To amma babu wani ingantaccen nassi da ya nuna wurin da wannan mahaɗar take.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, lokacin da suka kai wurin mahaɗar sai suka manta wannan kifin, wanda shi kuma ya fito daga cikin kwando ya faɗa cikin ruwan ya sami hanya kamar ɗakin ƙarƙashin ƙasa ko bututu ya yi ta tafiya a cikinta.
Ya zo a cikin hadisin Ubayyu cewa: Lokacin da Annabi Musa da yaronsa Yusha'u suka isa wurin wani dutse, sai suka sami inuwa suka kwanta daidai wata magudanar ruwa sai barci ya kwashe su. Wannan ruwa da yake kusa da su kuwa ana kiran sa da suna 'Ruwan rayuwa' domin duk wani abu da ya taɓa zai rayu ko da kuwa a da ya mutu. Sai kuwa ya taɓa wannan kifin nasu da ke cikin kwando, nan take kuwa ya fara watsal-watsal, ya fito daga kwando ya faɗa kogi, ya kama hanya ya yi tafiyarsa. Allah ya kame masa gudanar ruwa, sai ya yi kamar yana tafiya a cikin wani ɗaki. Annabi Musa yana barci, amma yaronsa ya farka ya ga abin da ya faru, sai kuma bai tashi Annabi Musa daga barci ba da niyyar idan ya farka zai sanar da shi, sai kuma ya manta bai sanar da shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ilimi ba ya samuwa sai an sha wahala. Da a ce akwai waɗanda za a ɗauke wa wahalar neman ilimi da annabawa ne, to amma ba a ɗauke musu ba.

2. Halaccin mutum ya ba da labarin halin da yake ciki wanda ya danganci ɗabi'a ta ɗan'adam kamar yunwa ko gajiya da makamantansu.

3. Neman ƙarin ilimi ga mai neman ilimi ya fi muhimmanci a kan shagaltuwa da karantar da shi ba tare da shi yana nema ba. Haɗa abubuwan biyu, watau neman ilimi da karantar da shi shi ya fi kamala.

4. Mustahabbi ne mutum ya ci abincinsa tare da hadiminsa.

5. Jingina wa Shaiɗan abin da zai faru marar dadi idan yana da alaƙa da sarayar da wani abu da Allah yake so, musamman babban abu irin wannan mai cike da mamaki, sannan kuma shi ne maƙasudin tafiyar tasu.

Suratul Kahf (62-64)

فَلَمَّا جَاوَزَا قَالَ لِفَتَىٰهُ ءَاتِنَا غَدَآءَنَا لَقَدْ لَقِينَا مِن سَفَرِنَا هَٰذَا نَصَبًا ﴿٦٢﴾ قَالَ أَرَءَيْتَ إِذْ أَوَيْنَآ إِلَى ٱلصَّخْرَةِ فَإِنِّى نَسِيتُ ٱلْحُوتَ وَمَآ أَنسَىٰنِيهُ إِلَّا ٱلشَّيْطَٰنُ أَنْ أَذْكُرَهُۥ ۚ وَٱتَّخَذَ سَبِيلَهُۥ فِى ٱلْبَحْرِ عَجَبًا ﴿٦٣﴾ قَالَ ذَٰلِكَ مَا كُنَّا نَبْغِ ۚ فَٱرْتَدَّا عَلَىٰٓ ءَاثَارِهِمَا قَصَصًا ﴿٦٤﴾

62. To lokacin da suka wuce (wannan wuri) sai (Musa) ya ce da yaronsa: "Kawo mana abincinmu, haƙiƙa mun haɗu da wahala cikin wannan tafiya tamu."

63. Sai (yaron) ya ce: "Ba ka gani ba lokacin da muka fake a daidai dutsen nan ai sai na manta da kifin, ba kuwa wani ne ya mantar da ni shi ba sai Shaiɗan, ya hana ni in tuna. Sai kuma ya kama hanyarsa cikin kogi, abin mamaki!"

64. (Musa) ya ce: "Wannan da ma shi ne abin da muke nema", Sai suka koma da baya suna bin sawunsu (ta inda suka fito).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa, Annabi Musa da yaronsa Yusha'u sun bar ƙarƙashin inuwar wannan dutse, sun kama hanya sun ci gaba da tafiya.
Ya zo a cikin hadisin Ubayyu cewa: "Sun yi tafiya ta tsawon kwana biyu. Bayan dare ya yi sun kwanta sun yi barci zuwa safiya. Da gari ya waye sai Annabi Musa ya ce wa yaronsa: "Kawo mana karin kumallonmu, haƙiƙa mun haɗu da wahala a cikin wannan tafiya tamu."
Ya zo a cikin wani hadisi cewa, Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai fara jin gajiya ba har sai da ya wuce wurin da aka umarce shi ya je.
To a nan ne yaronsa ya tuna abin da ya faru da kifi. Ya tabbatar wa da Annabi Musa cewa, ai lokacin da suna hutawa a ƙarƙashin dutsen nan, ya manta da wannan kifi a wannan wurin, kuma ya tashi ya faɗa cikin kogi ya tafi abinsa. Shi ma dai abin ya ba shi mamaki. Bai gaya masa ba ne domin Shaiɗan ya riga ya mantar da shi ya hana shi tunawa.
Da jin haka sai Annabi Musa ya ce, ai wannan abin nema ne ya samu, nan take suka juya suka koma inda suka baro, suna ta bin sawun ƙafafunsu don kada wurin ya ɓace musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ladabin magana ga malami da tausasa harshe yayin tambaya.

2. Tawali'un babba a gaban na ƙasa da shi wanda yake koyon wani ilimi a wurinsa. Domin babu shakka Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana gaba da Khadiru a matsayi da martaba.

3. Babban malami yana iya koyon abin da bai ƙware a kansa ba daga wajen wanda ya ƙware ko da kuwa bai kai shi ilimi ba.

4. Jingina ilimi zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da gode masa a kansa.

5. Ilimi mai amfani shi ne ilimin da yake shiryar da mai shi ga alheri, yake gargaɗin sa game da sharri. Duk ilimin da ba haka yake ba, to ko dai ya zamanto mai cutarwa ko kuma marar amfani.

6. Neman ilimi yana buƙatar haƙuri da juriya. Wanda ba ya da haƙurin zama da malami to zai yi asarar ilimi mai ɗimbin yawa da ke tare da shi.

7. Ilimi da gogewa a kan abubuwa suna ƙara wa mutum haƙuri da juriya.

8. Halaccin malami ya gindaya wa ɗalibi sharuɗɗa kafin ya fara ba shi ilimi, musamman yayin da sharuɗɗan nan suke tattare da maslahar shi ɗalibin a kan neman ilimin.

Suratul Kahf (65-70)

فَوَجَدَا عَبۡدٗا مِّنۡ عِبَادِنَآ ءَاتَيۡنَٰهُ رَحۡمَةٗ مِّنۡ عِندِنَا وَعَلَّمۡنَٰهُ مِن لَّدُنَّا عِلۡمٗا ٦٥ قَالَ لَهُۥ مُوسَىٰ هَلۡ أَتَّبِعُكَ عَلَىٰٓ أَن تُعَلِّمَنِ
مِمَّا عُلِّمۡتَ رُشۡدٗا ٦٦ قَالَ إِنَّكَ لَن تَسۡتَطِيعَ مَعِيَ صَبۡرٗا ٦٧ وَكَيۡفَ تَصۡبِرُ عَلَىٰ مَا لَمۡ تُحِطۡ بِهِۦ خُبۡرٗا ٦٨ قَالَ سَتَجِدُنِيٓ إِن
شَآءَ ٱللَّهُ صَابِرٗا وَلَآ أَعۡصِي لَكَ أَمۡرٗا ٦٩ قَالَ فَإِنِ ٱتَّبَعۡتَنِي فَلَا تَسۡـَٔلۡنِي عَن شَيۡءٍ حَتَّىٰٓ أُحۡدِثَ لَكَ مِنۡهُ ذِكۡرٗا ٧٠

65. To sai suka sami wani bawa daga bayinmu wanda Muka bai wa rahama daga gare Mu, kuma Muka koyar da shi wani ilimi daga wajenmu.

66. Musa ya ce da shi: "Shin na iya bin ka don ka koyar da ni (wani abu) daga abin da aka koyar da kai na shiriya?"

67. Ya ce da shi: "Lalle ba za ka iya haƙuri da ni ba.

68. "Ƙaƙa kuwa za ka yi haƙuri kan abin da ba ka kewaye da saninsa ba?"

69. (Musa) ya ce: "Za ka same ni mai haƙuri *in sha Allahu*, ba kuma zan saɓa wa umarninka ba."

70. Ya ce, "To idan ka bi ni kada ka tambaye ni game da kowane abu har sai na ba ka labari game da shi."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin labarin Annabi Musa da yaronsa Yusha'u da cewa, sun koma wurin da kifinsu ya ɓace, a nan ne kuma suka sami wani bawan Allah wanda Allah ya ba shi wata rahama daga gare shi, kuma ya sanar da shi wani ilimi na musamman daga wajensa. Hadisin Ubayyu ɗan Ka'ab ya nuna cewa, sun same shi a kan wata koriyar shimfiɗa a tsakiyar kogi ya lulluɓa da tufarsa, ya saka gefen tufar a ƙarƙashin ƙafafuwansa, ɗaya gefen kuma ya saka shi a ƙarƙashin kansa. Da Annabi Musa ya yi masa sallama sai ya buɗe fuskarsa ya ce masa: "Ina aka san sallama a ƙasarka? Wane ne kai?" Ya ce: "Ni ne Musa." Ya ce: "Musa na Banu Isra'ila?" Ya ce: "E, shi fa."

Wannan mutum, kamar yadda ingantattun hadisai suka nuna, shi ne Khadiru. Amma wannan ba shi ne sunansa na yanka ba, wannan laƙabinsa ne. Yawancin masana sun ce sunansa na yanka shi ne Balya ɗan Malkan.
Yawancin malamai suna ganin wannan bawan Allah annabi ne daga cikin annabawan Allah, kuma rahamar da Allah ya ce ya ba shi ita ce annabta da wahayi.
Daga nan sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙe shi cikin ladabi da biyayya cewa, ko zai iya bin sa don ya koyar da shi wani abu daga ilimin da Allah ya ba shi?
Sai Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya amsa ma Annabi Musa da cewa ba zai iya haƙurin zama da shi ba saboda abin da zai gani na iliminsa wanda ya sha bamban da nashi a zahiri. Ya nuna masa cewa, yana da wuya matuƙa ya yi haƙuri yayin da zai ga wasu abubuwa waɗanda bai gane kansu ba ko hikimar da ke cikinsu.
To amma sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ba shi tabbacin cewa, zai same shi mai haƙuri a kan duk abubuwan da zai iya gani, kuma zai yi masa biyayya ba tare da ya saɓa umarninsa ba.
Daga nan sai Khadiru ya faɗa masa sharaɗinsa wanda shi ne idan har ya bi shi sun tafi tare to duk abin da ya gan shi yana aikatawa kada ya yi masa wata tambaya a kai har sai shi ya bayyana masa manufar wannan abu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai yi haƙuri ya yi shiru bayan ya ga Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya lalata wa mutane jirgin ruwansu ba. Lalata dukiya laifi ne, amma Musa bai san dalilin da ya sa aka yi haka ba, shi ya sa ya yi magana.

2. Wajabcin bin al'amura a sannu da rashin saurin yin hukunci a kan abu ba tare da sanin maƙasudin aikata shi ba.

3. Ba a kama wanda ya manta da laifin mantuwa.4. Ya dace mutum ya koyi yin afuwa wajen mu'amala da mutane, kada kuma ya ɗora musu abin da ya fi ƙarfinsu.

Suratul Kahf (71-73)

فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَا رَكِبَا فِى ٱلسَّفِينَةِ خَرَقَهَا ۖ قَالَ أَخَرَقْتَهَا لِتُغْرِقَ أَهْلَهَا لَقَدْ جِئْتَ شَيْـًٔا إِمْرًا ﴿٧١﴾ قَالَ أَلَمْ أَقُلْ إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِىَ صَبْرًا ﴿٧٢﴾ قَالَ لَا تُؤَاخِذْنِى بِمَا نَسِيتُ وَلَا تُرْهِقْنِى مِنْ أَمْرِى عُسْرًا ﴿٧٣﴾

71. Sai suka tafi, har lokacin da suka shiga cikin jirgin ruwa, to sai ya huda shi; sai (Musa) ya ce: "Yanzu ka huda shi ne don ka nutsar da waɗanda suke cikinsa? Haƙiƙa ka zo da babban abu."

72. Ya ce: "Ban faɗa maka ba cewa kai ba za ka iya haƙuri da ni ba?"

73. (Musa) ya ce: "Kada ka kama ni da abin da na manta, kada kuma ka ɗora mini abu mai wahala game da al'amarina."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Khadiru. Bayan Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya karɓi buƙatar Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ta zama almajirinsa sai suka tafi.

Ya zo a cikin hadisin Ubayyu cewa,, sun tafi da ƙafafunsu har zuwa gaɓar kogi, sai suka ga ƙananan kwale-kwale waɗanda suke sufurin mutane daga wannan gaɓa zuwa ɗaya gaɓar. Sai ga wani jirgin ruwa ya zo wucewa, ta gabansu sai suka roƙi matuƙansa da su ɗauke su, sai suka gane Khadiru sai suka ce: "Wannan bawan Allah nan ne mutumin kirki". Sai suka ɗauke su kyauta ba ko kwabo. Ana tsakar tafiya Annabi Musa bai farga ba sai kawai ya ga har Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya cire allon wannan jirgi da gatari. Sai Musa ya ce: "Wane irin abu ne wannan ka aikata? Mutanen nan fa sun ɗauko mu kyauta, amma ka fasa musu jirgin ruwa, kana so ka nutsar da mutanen da ke cikinsa ne? Lalle ka zo da babban abu".
Sai Khadiru ya ce masa: "Ba na faɗi cewa, ba za ka iya haƙuri da ni ba?" Sai Annabi Musa ya ba shi haƙuri ya roƙe shi da kada ya kama shi da laifin da ya yi da mantuwa; kada kuma ya tsananta masa dangane da tarayya da shi.
Ya zo a cikin hadisin Ubayyu cewa, wani tsuntsu ya zo ya sauka a gefen wannan jirgin ruwa nasu ya tsattsago ruwan wannan kogi da bakinsa tsattsaga ɗaya ko biyu, sai Khadiru ya ce: "Ka san abin da wannan tsuntsun yake cewa?" Annabi Musa ya ce: "A'a". Sai ya ce: "Cewa yake: 'Iliminku ku biyun da kuke da shi idan an kwatanta shi da ilimin Allah bai wuce kamar abin da na raga da bakina daga ruwan wannan kogi ba."

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yaro da bai balaga ba tsarkakakke ne daga zunubai, ba za a fara rubuta komai game da ayyukansa ba har sai ya balaga.

2. A karo na biyu Annabi Musa bai ba da hanzari da mantuwa ba; ko dai saboda bai manta da sharaɗin da suka yi ba, sai dai ya ga munin kisan ƙaramin yaro ba zai iya yin shiru ba, ko kuma dai mantawar ya yi, amma ya ga ba daidai ne ya sake ba da hanzarin ya manta ba.

3. Ya zo a cikin hadisin Ubayyu cewa, ta farko dai mantuwa ce, amma ta biyu sharaɗi ne.

Suratul Kahf (74-76)

فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَا لَقِيَا غُلَٰمًا فَقَتَلَهُۥ قَالَ أَقَتَلْتَ نَفْسًا زَكِيَّةًۢ بِغَيْرِ نَفْسٍ لَّقَدْ جِئْتَ شَيْـًٔا نُّكْرًا ﴿٧٤﴾ ۞ قَالَ أَلَمْ أَقُل لَّكَ
إِنَّكَ لَن تَسْتَطِيعَ مَعِىَ صَبْرًا ﴿٧٥﴾ قَالَ إِن سَأَلْتُكَ عَن شَىْءٍۭ بَعْدَهَا فَلَا تُصَٰحِبْنِى ۖ قَدْ بَلَغْتَ مِن لَّدُنِّى عُذْرًا ﴿٧٦﴾

74. Sai suka ci gaba da tafiya har dai suka gamu da wani yaro, to sai ya kashe shi, (Musa) ya ce: "Yanzu ka kashe rai tsarkakakke ba tare da (ya kashe) wani rai ba? Haƙiƙa ka zo da wani abu mummuna!"

75. Ya ce: "Shin ban faɗa maka cewa lalle kai ba za ka iya haƙuri da ni ba?"

76. (Musa) ya ce: "Idan na sake tambayar ka wani abu bayansa, to kada ka tafi tare da ni; haƙiƙa ka sami (cikakken) hanzari a kaina."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya karɓi uzurin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) har ma sun ci gaba da tafiya bayan sun fito daga jirgin ruwa. To suna cikin tafiya a kan gaɓar kogi sai Khadiru ya hango wani yaro kafiri mai matuƙar wayo yana wasa cikin yara sai ya kamo shi ya kwantar da shi ya yanka shi da wuƙa ya cire kansa. Sai tsananin kishin addini ya kama Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) na ganin an yi wa yaro ƙarami irin wannan mummunan kisa, ya kasa jurewa sai ya ce masa: Yanzu ka kashe rai tsarkakakke ba tare da ya kashe wani rai ba? Haƙiƙa ka zo da wani abin ƙyama!.

Sai Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sake tuna masa da alƙawarinsu da cewa, ai da ma ya gaya masa cewa ba zai iya haƙuri da shi ba.
Sai Musa ya ce, yanzu kam in ya sake tambayar sa a nan gaba to ya yarda su rabu daga nan, domin ya yi masa duk wani uzuri da ya kamata ya yi masa, shi kuma ga shi ya saɓa wa umarninsa har sau uku.
Ya zo cikin hadisin Ubayyu, Annabi (ﷺ) ya ce: "Allah ya ji ƙan Musa, ba domin ya yi gaggawa ba da ya ga abin mamaki, sai dai ya ji kunyar abokin tafiyarsa ya ce: "Idan na sake tambayar ka wani abu nan gaba, to kada ka tafi tare da ni, haƙiƙa ka sami cikakken hanzari a kaina." Da ya yi haƙuri da ya sha mamaki.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin illar rowa da rashin karrama baƙo. Ƙatada yana cewa,: "Mafi sharrin gari shi ne wanda ba a karrama baƙo a cikinsa, kuma ba a san haƙƙin matafiyi ba."

2. Wanda ya shiga cikin tsananin yunwa ya halatta gare shi ya roƙi abinci wajen mutane.

3. Wajibi ne a kan mutanen garin nan su karɓi baƙuncin baƙinsu, don haka Annabi Musa da Khadiru sun nemi a ba su haƙƙinsu ne a shari'ance.

4. Ana kallon abubuwa ne a zahirinsu a yi musu hukunci; abin nan ya shafi dukiya ne ko jini ko makamantansu. Don haka Annabi Musa ya yi wa Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) inkarin lalata jirgin ruwa da kashe ƙaramin yaro. Domin a zahiri duk waɗannan abubuwa munana ne, da Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zai ga irin wannan ya faru a wani wuri to ba zai yiwu ya yi shiru ba tare da ya tsawatar ba, don haka a nan ma sai ya kasa jurewa ya jira bayani daga Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai da ya yi magana a kai.

5. Fahimtar wata babbar ƙa'ida ta shari'a mai muhimmanci, ita ce: Ya halatta a kawar da babbar ɓarna ta hanyar aikata ƙaramar ɓarna, kamar yadda za a tabbatar da babbar maslaha ta hanyar rasa wata ƙaramar maslaha. Kashe ƙaramin yaro ɓarna ce, to amma ɓarnar a ƙyale shi har ya girma ya salwantar da addinin iyayensa ta fi girma, don haka Khadiru ya kashe shi da umarnin Allah.

6. Ya halatta mutum ya aikata wani aiki a kan dukiyar da ba tashi ba, ba kuma da izinin mai ita ba, domin tabbatar da wata maslaha da kawar da ɓarna, ko da kuwa aikin nasa zai haifar da salwantar wani ɓangare na wannan dukiyar, kamar gobar ta kama gidan wani ba yanan, kuma ba zai yiwu a kubutar da dukiyar mutumin ba har sai an rushe wani bangare na gidan, to ya halatta a rushe ba da izininsa ba, domin ceto da sauran dukiyarsa. [Dubi, As-Si'idi, *Tafisirinsa*, shafi na 482].

Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya lalata wannan jirgin ruwan ba da izinin masu shi ba, domin ya kuɓutar da shi daga azzalumin sarkin da yake ƙwace lafiyayyun jirage, domin ya san za su so hakan ba za su ƙi ba saboda maslaharsu..

7. Halaccin gudanar da sana'a a cikin ruwa.

8. Miskini kan iya mallakar wani abu na dukiya wanda ba zai ishe shi rayuwa ba, wannan ba ya fitar da shi daga sahun miskinai.

9. Kisan rai ba bisa haƙƙi ba yana cikin manyan laifuffuka.

10. Kisa domin ramuwa (ƙisasi) ba wani mummunan abu ne ba.

11. Allah yana tsare wa bawansa nagari zurriyyarsa ko da a bayansa ne.

12. Hidima ga mutanen kirki da masu alaƙa da su abu ne mai kyau a shari'a.

13. Waɗannan abubuwa da suka gudana a hannun wannan bawan Allah Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suna nuna cewa, shi Annabi ne na Allah. Wannan ita ce maganar mafi yawancin malamai kamar yadda Ƙurɗubi da Abu Hayyan da Al-Aini da Alusi suka ambata. Suka kafa hujja kamar haka:
• Ayyukan da Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi na lalata jirgin ruwa da kashe rai ba za su auku ba sai ta hanyar wahayi, kamar yadda Ƙurɗubi ya faɗa.
• Faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cewa, "ya ba shi rahama daga gare shi ya koyar da shi wani ilimi daga wajensa". Malamai da yawa sun fassara 'rahama' da wahayi ko annabta.
• Faɗar Annabi Musa cewa; "Shin na iya bin ka don ka koyar da ni daga abin da aka koyar da kai na shiriya?" Annabi ba zai zama mabiyin wani wanda ba annabi ba komai darajarsa a wurin Allah.
• Faɗar Allah ga Annabi Musa: "E, ina da wani bawa a mahaɗar koguna biyu ya fi ka ilimi." Ibnu Hajar ya ce: "Ta yaya wanda ba annabi ba zai fi annabi ilimi?" Ya ce: "Zahirin wannan magana tana nuna Khadir Annabi ne manzo, domin da ba haka ne ba to da an fifita babba a kan wanda ya fi shi ɗaukaka, haka kuwa ba daidai ne ba."
• Faɗarsa: "Ban aikata haka ba ne da raɗin kaina", ya tabbatar da annabcin Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kuma ana yi masa wahayi a ba shi umarnin aikata wasu ayyuka.
• Faɗarsa: "Wannan shi ne rabuwarmu da kai." Da a ce Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba annabi ne ba da ba zai zaɓi rabuwa da annabin Allah ba.

Suratul Kahf (77-82)

فَٱنطَلَقَا حَتَّىٰٓ إِذَآ أَتَيَآ أَهۡلَ قَرۡيَةٍ ٱسۡتَطۡعَمَآ أَهۡلَهَا فَأَبَوۡاْ أَن يُضَيِّفُوهُمَا فَوَجَدَا فِيهَا جِدَارٗا يُرِيدُ أَن يَنقَضَّ فَأَقَامَهُۥۖ قَالَ لَوۡ شِئۡتَ لَتَّخَذۡتَ عَلَيۡهِ أَجۡرٗا ٧٧ قَالَ هَٰذَا فِرَاقُ بَيۡنِي وَبَيۡنِكَۚ سَأُنَبِّئُكَ بِتَأۡوِيلِ مَا لَمۡ تَسۡتَطِع عَّلَيۡهِ صَبۡرًا ٧٨ أَمَّا ٱلسَّفِينَةُ فَكَانَتۡ لِمَسَٰكِينَ يَعۡمَلُونَ فِي ٱلۡبَحۡرِ فَأَرَدتُّ أَنۡ أَعِيبَهَا وَكَانَ وَرَآءَهُم مَّلِكٞ يَأۡخُذُ كُلَّ سَفِينَةٍ غَصۡبٗا ٧٩ وَأَمَّا ٱلۡغُلَٰمُ فَكَانَ أَبَوَاهُ مُؤۡمِنَيۡنِ فَخَشِينَآ أَن يُرۡهِقَهُمَا طُغۡيَٰنٗا وَكُفۡرٗا ٨٠ فَأَرَدۡنَآ أَن يُبۡدِلَهُمَا رَبُّهُمَا خَيۡرٗا مِّنۡهُ زَكَوٰةٗ وَأَقۡرَبَ رُحۡمٗا ٨١ وَأَمَّا ٱلۡجِدَارُ فَكَانَ لِغُلَٰمَيۡنِ يَتِيمَيۡنِ فِي ٱلۡمَدِينَةِ وَكَانَ تَحۡتَهُۥ كَنزٞ لَّهُمَا وَكَانَ أَبُوهُمَا صَٰلِحٗا فَأَرَادَ رَبُّكَ أَن يَبۡلُغَآ أَشُدَّهُمَا وَيَسۡتَخۡرِجَا كَنزَهُمَا رَحۡمَةٗ مِّن رَّبِّكَۚ وَمَا فَعَلۡتُهُۥ عَنۡ أَمۡرِيۚ ذَٰلِكَ تَأۡوِيلُ مَا لَمۡ تَسۡطِع عَّلَيۡهِ صَبۡرٗا ٨٢

77. Sai suka ci gaba da tafiya har suka iso ga mutanen wata alƙarya, sai suka nemi mutanen alƙaryar su ciyar da su, to sai suka ƙi su karɓi baƙuntarsu, sai suka samu wani garu a alƙaryar yana haramar rugujewa sai (Khadiru) ya tashe shi, sai (Musa) ya ce: "Da ka ga dama ai da sai ka karɓi lada a kansa." (Watau aikin tayarwar).

78. Ya ce: "Wannan ita ce rabuwata da kai. Zan ba ka labarin abin da ka kasa haƙuri a kansa."

79. "To game da shi jirgin ruwan nan ya kasance na wasu miskinai ne da suke aiki a cikin kogi, to sai na yi nufin in lalata shi domin kuwa a gabansu akwai wani sarki da yake ƙwace kowane jirgin ruwa (lafiyayye).

80. “To amma kuma game da shi yaron nan, iyayensa sun kasance muminai ne, sai muka ji tsoron kada ya afkar da su cikin shisshigi da kafirci.

81. “Sai muka yi nufin Ubangijinsu Ya musanya musu (wani ɗa) wanda ya fi tsarkaka ya kuma fi shi tausayi.

82. “To game da shi garun nan kuwa ya kasance na wasu yara ne marayu a cikin wannan birnin, a ƙarƙashinsa kuwa da akwai wata taska tasu, mahaifinsu kuma ya kasance mutumin kirki ne, to sai Ubangijinka Ya nufi su girma su cika hankalinsu su, kuma fito da taskarsu, don rahama daga Ubangijinka. Ban aikata haka ba ne da raɗin kaina. Wannan shi ne fassarar abin da ka kasa haƙuri a kansa.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa sun ci gaba da tafiya har suka iso garin wasu marowatan mutane, suka nemi mutanen garin su ba su abinci, to amma sai mutanen suka ƙi karɓar baƙuncinsu. To sai Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka sami wani garu na garin yana shirin faɗuwa, sai Khadiru ya miƙar da shi, sai Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna masa cewa, ai da ya ga dama da ya karɓi lada a kan wannan aiki da ya yi musu, domin sun nemi abinci a wajensu sun hana su, don haka bai dace ya yi musu aiki kyauta ba, sannan ga shi suna buƙatar abin sayen abinci da za su ci.
Sai Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ce masa, to wannan karon lokacin rabuwarsu ya yi, kuma zai bayyana masa fassarar duk abubuwan da ya kasa haƙuri a kansu har sai da ya yi magana.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fassara ayyukansa ɗaya bayan ɗaya.
Jirgin ruwa da ya lalata dai na wasu miskinai ne da suke aiki da shi a wannan ruwan suna samun abin da suke rayuwa da shi, to amma a hanyar da suka biyo akwai wani azzalumin sarki wanda duk inda ya ga lafiyayyen jirgi to zai ƙwace shi; ga shi su kuma raunana ne ba za su iya kare jirginsu ba. Sai Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ce, bari ya lalata wani ɓangare na jirgin yadda idan wannan sarki ya gan shi a lalace ba zai yi shaʾawarsa ba har ya ƙwace musu. To wannan ita ce hikimarsa ta lalata wannan jirgin.
Shi kuma yaron da ya kashe yadda labarinsa yake shi ne, iyayensa muminai ne, shi kuma Allah ya riga ya san kafiri zai taso, sai Khadiru ya ji tsoron idan yaron nan ya girma zai mayar da iyayen nan nasa kafirai masu shisshigi cikin iyakokin Allah saboda tsananin soyayyar da suke yi masa. Kuma ya yi fatan Allah zai canja musu shi da wani ɗan wanda ya fi shi alheri da addini da kirki da tsarkaka daga zunubai da tausaya wa mahaifansa.
Dangane da garun da ya miƙar, shi kuma na wasu ƙananan yara ne marayu, mahaifinsu wani mutumin kirki ne a garin. Kafin ya rasu ya binne musu dukiyarsu a ƙarƙashin wannan garun, da nufin idan har Allah ya sa suka girma suka yi hankali sai su tono dukiyarsu. To amma da ya ƙyale garun ya faɗi, da dukiyar ta bayyana kuma da mutanen garin ne za su wawashe ta. To duk wannan tsari rahamar Allah ce gare su.
Sai Khadiru (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tabbatar wa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa, duk waɗannan abubuwa da ya ga ya aikata ba gaban kansa ne ya yi su ba, watau da umarnin Allah ya yi su. Ya shaida masa cewa, wannan shi ne fassarar abin da ya kasa haƙuri a kansa.

Suratul Kahf (83-85)

وَيَسْـَٔلُونَكَ عَن ذِى ٱلْقَرْنَيْنِ ۖ قُلْ سَأَتْلُوا۟ عَلَيْكُم مِّنْهُ ذِكْرًا ﴿٨٣﴾ إِنَّا مَكَّنَّا لَهُۥ فِى ٱلْأَرْضِ وَءَاتَيْنَـٰهُ مِن كُلِّ شَىْءٍ سَبَبًا ﴿٨٤﴾
فَأَتْبَعَ سَبَبًا ﴿٨٥﴾

83. Suna kuma tambayar ka game da Zulƙarnaini; ka ce (da su): “Ba da daɗewa ba zan ba ku labari a kansa.”

84. Lalle Mu Muka kafa shi a bayan ƙasa, Muka kuma ba shi hanyar cimma duk wani muradinsa.

85. Sai ya bi hanya.

Daga aya ta 83 har zuwa aya ta 98 Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin Zul-Ƙarnaini ne domin amsa tambayar wasu daga cikin kafiran Ƙuraishawa ga Annabi (ﷺ) game da shi, don ya zama tunatarwa da waʾazantarwa gare su.
Zul-ƙarnaini dai wani Sarki ne mumini mai Kaɗaita Allah, wanda ya yi imani da ranar lahira. Allah ya ba shi ƙarfin mulki har ya ci garuruwa masu yawa da yaƙi. Allah kuma ya ba shi duk wani abu da mai mulki a zamaninsa yake buƙata don wanzuwar mulkinsa da tabbatar da adalci a bayan ƙasa. Ya kasance mai kira ne zuwa ga Allah, da yaƙi da duk wani mai bautar wani ba Allah ba. Zul-Ƙarnaini ya kewaye duniya da yawo, ya isa yammacin duniya, daga nan ya dawo ya danna gabashinta inda ya isa wurin da ya gina babbar ganuwa tsakanin ƙabilun Yajuju da Majuju da sauran maƙotansu. Yana karɓar umarni ne ta hanyar wahayi da ake yi masa kai-tsaye (idan shi annabi ne), ko ta hanyar wani annabi da ke tare da shi a cikin rundunarsa. Da yawa daga cikin malaman tafsiri suna cewa, Zul-Ƙarnaini shi ne Alexander ɗan Philip mutumin Maƙduniya (Macedon) da ke masarautar Girika (Greek). Kuma babban wazirinsa, suka ce shi ne Aristatalis (Aristotle) shahararren malamin nan na falsafa. Sai dai wannan maganar tasu kuskure ne babba, domin dalilai kamar haka:

1. Zul-Ƙarnaini Sarki ne mumini wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira. Alexander kuwa mushiriki ne mai bautar gumaka da taurari.

2. Alexander ba a kiran sa da suna Zul-Ƙarnaini.

3. Yaƙe-yaƙen Alexander ba su kai ƙasashen Turkawa ba, iyakacinsu ƙasar Farisa.

4. Alexander ba shi ne ya gina babbar ganuwar da ke tsakanin Yajuju da Majuju da sauran ƙabilu maƙotansu ba.

5. Alexander ya rayu ne gabanin haihuwar Annabi Isa da kimanin shekara ɗari uku, yayin da shi kuma Zul-Ƙarnaini ya shuɗe da daɗewa. [Dubi, Ibnu Taimiyya, *Al-Jawabus Sahih*, Juzuʾi na 1, shafi na 346-347].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ban sani ba, shin Tubbaʾu laʾananne ne ko aʾa? Ban kuma sani ba, shin Zul-Ƙarnaini annabi ne ko aʾa?....” [Abu Dawud #4674].

An tambayi Sayyidina Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) cewa,: Shin Zul-Ƙarnaini annabi ne? Sai ya ce: “Ya kasance bawa ne na ƙwarai, ya so Allah sai shi ma Allah ya so shi, ya yi nasiha don Allah sai shi ma Allah ya yi masa nasiha, sai ya tura shi wajen mutanensa, suka yi masa duka guda biyu a kansa, don haka ne ake kiran sa Zul-Ƙarnaini....” [Ibnu Jarir, Juzuʾi na 16, shafi na 16].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya ba shi mulki mai ƙarfi a bayan ƙasa, don haka ya riƙi duk wani abu da Allah ya hore masa ya kama hanya don cimma burinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zul-Ƙarnaini da rundunarsa sun danna sun yi yamma har suka dangana da wani ruwa wanda ba za a iya wuce shi ba a wancan zamanin. Ya ga wani marmaro na ruwa mai taɓo mai launin baƙi, gaban wannan marmaro wani kogi ne babba, to sai ake ganin kamar rana idan ta zo faɗuwa tana faɗuwa ne a cikin wannan

marmaro na taɓo domin shi ne da farko, alhalin ita rana ba ta fita daga falaki na huɗu wanda shi ne magudanarta.

2. Umarnin Allah ga Zul-Ƙarnaini na ya kashe mutanen da ya samu a wannan wuri ya nuna cewa, mutane ne kafirai maɓarnata waɗanda suka cancanci azabar kisa idan har ba su canza hali ba.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana da Zul-Ƙarnaini ta hanyar wahayi, idan ya tabbata shi annabi ne, ko kuma ta hanyar wani annabi da yake tare da shi a cikin rundunarsa.

4. Mulki yana ɗorewa ne da abubuwa biyu: Na farko, jarumta, watau hukunta duk wani mai laifi ba sani ba sabo. Yin haka shi ne zai jefa tsoro a zuciyar duk wani mai shirin aikata ɓarna. Na biyu shi ne karamci, watau kyautatawa da ihsani ga duk wanda ya cancanci a kyautata masa saboda kyawawan ayyukansa da ƙwazonsa. Idan an rasa waɗannan abubuwa biyu ko ma ɗaya daga cikinsu to mulki ba zai ɗore ba. Zul-Ƙarnaini ya haɗa duk waɗannan abubuwa guda biyu kamar yadda aya ta 87 da ta 88 suka nuna.

Suratul Kahf (86-89)

حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ مَغۡرِبَ ٱلشَّمۡسِ وَجَدَهَا تَغۡرُبُ فِي عَيۡنٍ حَمِئَةٖ وَوَجَدَ عِندَهَا قَوۡمٗاۗ قُلۡنَا يَٰذَا ٱلۡقَرۡنَيۡنِ إِمَّآ أَن تُعَذِّبَ وَإِمَّآ أَن تَتَّخِذَ فِيهِمۡ حُسۡنٗا ٨٦ قَالَ أَمَّا مَن ظَلَمَ فَسَوۡفَ نُعَذِّبُهُۥ ثُمَّ يُرَدُّ إِلَىٰ رَبِّهِۦ فَيُعَذِّبُهُۥ عَذَابٗا نُّكۡرٗا ٨٧ وَأَمَّا مَنۡ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَلَهُۥ جَزَآءً ٱلۡحُسۡنَىٰۖ وَسَنَقُولُ لَهُۥ مِنۡ أَمۡرِنَا يُسۡرٗا ٨٨ ثُمَّ أَتۡبَعَ سَبَبًا ٨٩

86. Har sai da ya isa mafaɗar rana, sai ya same ta tana faɗuwa ne cikin wani marmaro haɗe da baƙin taɓo mai wari, ya kuma sami wasu mutane a wurinta, Muka ce: “Ya Zulƙarnaini, ko dai ka azabtar (da su), ko kuma ka kyautata musu.”

87. (Zulƙarnaini) ya ce: “Amma wanda ya yi zalunci to za mu azabtar da shi, sannan a mayar da shi zuwa ga Ubangijinsa (shi ma) Ya yi masa mummunar azaba.

88. “Amma kuma wanda ya yi imani ya kuma yi aiki nagari, to yana da mafi kyan sakamako, kuma za mu faɗa masa tattausar (magana) game da al’amarinmu.”

89. Sannan ya kama hanya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Zul-Ƙarnaini ya ci gaba da tafiya a bayan ƙasa da rundunarsa, har ya isa ƙarshen ƙasa ta nahiyar yamma inda ɗan’adam a lokacin ba zai wuce shi ba. Kuma nan ne mafaɗar rana, ya gan ta tana faɗuwa cikin wani marmaro wanda yake cakuɗe da taɓo mai launin baƙi mai wari. A nan ne ya ga wasu mutane kafirai waɗanda suke bautar gumaka ba Allah ba, suna rayuwa kamar dabbobi ba addini. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Zul-Ƙarnaini zaɓi cewa, ko dai ya azabtar da mutanen nan ta hanyar kisa ko waninsa idan sun ƙi yin imani, ko kuma ya bi su ta lalama da kyautatawa.
Sai Zul-Ƙarnaini ya bayyana cewa, duk wanda ya yi shirka da Allah ya doge a kan kafirci bayan an yi masa wa’azi an nuna masa gaskiya, to zai yi masa azaba a nan duniya ta hanyar kisa, sannan ya koma ga Ubangijinsa ranar alƙiyama ya yi masa mummunar azaba.
Ya kuma bayyana cewa, daga cikinsu duk wanda ya yi imani da Allah ya yi kyakkyawan aiki, to yana da sakamakon gidan Aljanna, sannan zai faɗa masa tattausar magana daga lamarinsa.

Sai kuma Zul-Ƙarnaini ya ci gaba da tafiyarsa da sojojinsa bayan ya gama tabbatar da umarnin Allah a kan waɗannan mutanen.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samarwa da ɗan'adam inuwoyi don fakewa daga zafin rana ni'ima ce daga Allah, ba don ya yi masa ita ba to da zai rasa wurin fakewa ne.

2. Cikakken ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda ya kewaye komai da komai na sarari da na ɓoye.

Suratul Kahf (90-91)
حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ مَطۡلِعَ ٱلشَّمۡسِ وَجَدَهَا تَطۡلُعُ عَلَىٰ قَوۡمٖ لَّمۡ نَجۡعَل لَّهُم مِّن دُونِهَا سِتۡرٗا ٩٠ كَذَٰلِكَۖ وَقَدۡ أَحَطۡنَا بِمَا لَدَيۡهِ خُبۡرٗا ٩١

90. Har dai lokacin da ya isa mahudar rana, ya same ta tana ɓullowa ne a kan wasu mutane da ba Mu sanya musu wata kariya ba daga gare ta.

91. Kamar haka (ya yi hukunci watau irin yadda ya yi a mafaɗar rana), haƙiƙa kuma Mun kewaye da sanin (duk) abin da ke tare da shi (Zulƙarnaini).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Zul-Ƙarnaini ya ci gaba da tafiyarsa a bayan ƙasa inda ya dawo kuma ya nufi nahiyar yamma, watau mahudar rana. Ya kuma sami rana tana fitowa a kan wasu mutane waɗanda ba su da wata kariya da za ta kare su daga zafin rana, domin ba su da gidaje kuma inda suke babu bishiyoyi da za su fake a inuwoyinsu, domin a ƙasarsu babu dutse babu bishiya, kuma ƙasar ba za ta ɗauki gine-gine ba.
Al-Hasanul Basri ya ce: "Ƙasarsu ta kasance ba ta ɗaukar gini a kanta, sun zamanto duk sa'adda rana ta fito musu sai su gudu su shiga cikin ruwa, idan ta faɗi sai su fito su ci gaba da kiwo a waje kamar dabbobi."
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, rayuwar waɗannan mutanen irin rayuwar mutanen nan ne da Zul-Ƙarnaini ya samu a mafaɗar rana, su ma kafirai ne kuma masu aikata laifuffuka da ɓarna a bayan ƙasa. Don haka su ma ya tafiyar da lamarinsu kamar yadda ya yi tare da waɗancan mutanen na farko.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna yana sane da halayen da Zul-Ƙarnaini yake ciki shi da rundunarsa, yana kuma yi musu jagora.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin hanyoyin ci gaban al'umma fahimtar yaren wasu al'ummu ban da nasu, domin amfanuwa da hikimomi da ƙwarewa da ke cikin waɗansu al'ummu. Rashin fahimtar al'umma ga wani harshe sai nata kaɗai alama ce ta ci baya cikin wannan al'ummar.

2. Duk yadda wata daula ta kai wajen ƙarfin tattalin arziki da wadatar ma'adanai idan ana son ci gabanta wajen ayyukan raya ƙasa da gina al'ummarta, to dole ne jama'ar ƙasar sai sun taimaka mata, kowa daidai gwargwadon abin da Allah ya hore masa; wani da iliminsa; wani da ƙarfinsa; wani kuma da dukiyarsa. To sai ka ga ƙasa ta ci gaba, rayuwar al'umma ta yi kyau.

3. Yana da kyau idan shugaba ya ba wa ma'aikatansa wani aiki, to shi ma ya yi tarayya da su wajen zartar da wannan aikin ko da kuwa da sa ido ne; yin hakan shi zai ƙara wa ma'aikatansa kuzari da karsashin

gudanar da aikinsu, kamar yadda hakan na iya taimaka musu wajen inganta aikin da zartar da shi yadda ya kamata.

4. Wajibi ne shugaba ya zamanto mai kamewa daga taɓa dukiyar al'ummarsa; idan yana da wadatar dukiya to ya yi musu aiki ba tare da ya karɓi haraji daga hannunsu ba; wannan yana daga cikin adalci da karamcin da shugaba zai nuna.

5. Akwai wasu masana da suka ce, ganuwar da Sarki Zul-Ƙarnaini ya gina ita ce babbar ganuwar ƙasar Sin (China). Wannan magana ce mai rauni ƙwarai, saboda dalilai kamar haka:
• Zul-Ƙarnaini ya gina ganuwarsa ne tsakanin wasu mutane da ƙabilun Yajuju da Majuju. Amma ganuwar Sin (China) sarakunansu ne suka gina ta, domin kare garuruwansu daga hare-haren mayaƙa.
• Ganuwar Zul-Ƙarnaini ya gina ta ne da guntattakin ƙarafuna da narkakkiyar dalma, amma babbar ganuwar ƙasar Sin an gina ta ne da duwatsu da laka.
• Ganuwar Zul-Ƙarnaini ya gina ta ne tsakanin duwatsu guda biyu, domin ya toshe hanyar da Yajuju da Majuju suke bi su kai hare-hare ga maƙotansu. Amma ita babbar ganuwar ƙasar Sin an gina ta ne a kan duwatsu da kwazazzabai da hanyoyi, ta kuma faro ne tun daga gabashin ƙasar Sin har ya zuwa yammacinta, watau tafiyar dubban mila-milai.
• Ganuwar Zul-Ƙarnaini babu mai iya huda ta har sai wa'adin da Allah ya ɗeba mata ya cika, watau gab da tashin alƙiyama. Amma ita babbar ganuwar ƙasar Sin ta daɗe da farfashewa, kuma mutane na ta shige-da-ficensu ta samanta.

Suratul Kahf (92-98)

ثُمَّ أَتۡبَعَ سَبَبًا ٩٢ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ بَيۡنَ ٱلسَّدَّيۡنِ وَجَدَ مِن دُونِهِمَا قَوۡمٗا لَّا يَكَادُونَ يَفۡقَهُونَ قَوۡلٗا ٩٣ قَالُواْ يَٰذَا ٱلۡقَرۡنَيۡنِ إِنَّ يَأۡجُوجَ وَمَأۡجُوجَ مُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَهَلۡ نَجۡعَلُ لَكَ خَرۡجًا عَلَىٰٓ أَن تَجۡعَلَ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَهُمۡ سَدّٗا ٩٤ قَالَ مَا مَكَّنِّي فِيهِ رَبِّي خَيۡرٞ فَأَعِينُونِي بِقُوَّةٍ أَجۡعَلۡ بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَهُمۡ رَدۡمًا ٩٥ ءَاتُونِي زُبَرَ ٱلۡحَدِيدِۖ حَتَّىٰٓ إِذَا سَاوَىٰ بَيۡنَ ٱلصَّدَفَيۡنِ قَالَ ٱنفُخُواْۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَعَلَهُۥ نَارٗا قَالَ ءَاتُونِيٓ أُفۡرِغۡ عَلَيۡهِ قِطۡرٗا ٩٦ فَمَا ٱسۡطَٰعُوٓاْ أَن يَظۡهَرُوهُ وَمَا ٱسۡتَطَٰعُواْ لَهُۥ نَقۡبٗا ٩٧ قَالَ هَٰذَا رَحۡمَةٞ مِّن رَّبِّيۖ فَإِذَا جَآءَ وَعۡدُ رَبِّي جَعَلَهُۥ دَكَّآءَۖ وَكَانَ وَعۡدُ رَبِّي حَقّٗا ٩٨

92. Sannan ya kama hanya.

93. Har ya iso (wani gari) tsakanin duwatsu biyu, ya kuma sami wasu mutane a gabansu (watau duwatsun) waɗanda ba sa fahimtar wata magana.

94. Suka ce: "Ya Zulƙarnaini, lalle Yajuju da Majuju (mutane ne) masu ɓarna a bayan ƙasa, to ko za mu iya biyan ka wata jinga don ka sanya wani shamaki tsakaninmu da su?"

95. Ya ce, "Abin da Ubangijina Ya ba ni ya fi (abin da za ku ba ni), sai dai ku taimake ni da ƙarfi (don) in sanya shamaki tsakaninku da su.

96. "Ku kawo mini guntattakin ƙarafa"; har dai lokacin da ya daidaita (ginin da) duwatsun nan biyu, sai ya ce: "Ku hura wuta da zugazuginku"; har dai yayin da ya mai da shi wuta, sai ya ce: "Ku kawo min narkakkiyar dalma in zuba a kansu."

97. Saboda haka ba su samu ikon su haura shi ba, ba su kuma sami ikon huda shi ba.

98. Ya ce, “Wannan rahama ce daga Ubangijina; sai dai idan alƙawarin Ubangijina ya zo, (watau tashin alƙiyama) to zai mai da shi daga-daga; alƙawarin Ubangijina kuwa ya tabbata gaskiya ne.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Zul-Ƙarnaini ya ci gaba da tafiyarsa tare da sojojinsa har ya kai ga wata hanya tsakanin wasu duwatsu biyu, a kusa da su kuma ya sami wasu mutane waɗanda ba sa fahimtar wani yaren da ba nasu ba. Da suka fahimci cewa, Zul-Ƙarnaini Sarki ne adali sai suka kai masa kukansu na wasu ƙabilu biyu da ake kira Yajuju da Majuju, suka shaida masa cewa, su waɗannan ƙabilu maɓarnata ne a bayan ƙasa, suna kawo wa sauran ƙabilun yankin hare-hare, suna kashe na kashewa su wawashe wa jamaʾar gari dukiyoyinsu su lalata musu gonakinsu.
Yajuju da Majuju dai suna daga cikin zurriyyar Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Kamannin halittarsu irin ta sauran ‘yanʾadam ce babu wani bambanci, suna da yawan gaske da yawan ɓarna da taʾadi a bayan ƙasa. Hakan ya sa ƙabilun suka nemi Zul-Ƙarnaini da ya taimaka musu wajen magance yawan hare-hare da suke kawo musu. Suka tambaye shi cewa, ko zai yarda su ba shi wani lada don ya sanya wani shamaki tsakaninsu da su? Sai Zul-Ƙarnaini ya amsa musu da cewa, abin da Allah ya ba shi na ƙarfin mulki ya fi duk wani abu da za su tara masa, taimakon da kawai yake nema a wajensu shi ne na maʾaikata da kayan aiki na gini da sauran abin da aikin gina ganuwar zai buƙata, shi kuma zai gina musu wannan shamaki a tsakaninsu.
Ya umarce su da su kawo masa guntattakin ƙarafa manya-manya, suka kuwa kawo masa, nan take ya fara gina ganuwa tsakanin waɗannan duwatsu guda biyu, har ginin ya kai daidai tsawonsu, sai ya umarci maʾaikatansa da su kunna wa guntattakin ƙarafan nan wuta har sai da suka yi ja jawur, sai ya umarce su su kawo masa narkakkiyar dalma don ya zuba ta a kai. Bayan haka da ta huce ta daskare sai ta zama wani curarren abu guda mai matsanancin ƙarfi wanda ya zama ganuwa tsakanin Yajuju da Majuju da sauran ƙabilu mazauna wannan wuri.
Allah ya bayyana cewa, tun bayan gina wannan ganuwa Yajuju da Majuju ba su sami ikon haura ta ba da dawakansu da makamansu domin kai hare-hare, kamar yadda suka saba a baya, haka kuma ba su sami ikon huda ta ta ƙasa da digoginsu ba.

An karɓo daga Zainab ‘Yar Jahshin (رضى الله عنها) ta ce: Wata rana Annabi (ﷺ) ya shigo mata a firgice yana cewa,: “*La Ilaha Illallahu*, Larabawa sun banu daga wani sharri da ya kusanto! A yau an buɗe wata ‘yar ƙofa daga ganuwar Yajuju da Majuju kamar haka.” Sai ya haɗa babban ɗan yatsansa na hannu da mai bi masa ya yi ƙawanya da su. Sai Zainab ta ce: “Ya Manzon Allah, yanzu za a halaka mu alhalin a cikinmu akwai mutanen kirki?” Sai ya ce: “Naʾam, idan na banza suka yi yawa.” [Bukhari #3346 da Muslim #2880].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana cewa,, yayin da Zul-Ƙarnaini ya dubi aikin wannan ganuwa ya ga ya kammala kamar yadda ya tsara, sai ya bayyana cewa, wannan rahamar Ubangijinsa ce ga mutane da ya tausaya musu, don haka ya tsare su daga sharrin Yajuju da Majuju da wannan ganuwar. To amma fa duk lokacin da waʾadin da Allah ya ajiye na fitowarsu ya zo, watau gabanin tashin alƙiyama, to zai baje wannan ganuwar ya mayar da ita daidai da ƙasa kamar ba a taɓa gina wani abu a wurin ba, kuma tabbas alƙawarin Allah gaskiya ne sai ya tabbata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da busar ƙaho don tashin matattu domin hisabi.

2. Allah ya tabbatar da tashin kowa da komai da tattara su wuri guda ranar alƙiyama, don yi musu hisabi da sakamako a kan ayyukansu masu kyau da marasa kyau.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a ranar alƙiyama zai bijiro da wutar Jahannama ga kafiri, domin mutum ya yi ƙoƙari ya gyara tsakaninsa da Allah tun a nan duniya, ya kuma ji tsoron wannan ranar, ya yi mata tanadi mai kyau.

4. Kafirai idanunsu a makance suke ba sa ganin ayoyin Allah da ya saka a cikin halittunsa a ƙasa da sama masu nuna Ɗayantakarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da wani abokin tarayya ba. Hakanan idanunsu sun makance ba sa ganin abin da Alƙur'ani ya ƙunsa na wa'azi da hikima, don haka ba sa fahimtar komai.

5. Waɗanda suka bauta wa wasu ba Allah ba, ko suka tara shi da wasu ababan bauta, to ba za su amfane su da komai ba a ranar alƙiyama, ba kuma za su kare musu azabar Allah ba, ko da kuwa waɗanda suka bauta wa ɗin suna da kusanci da Allah, kamar mala'iku da annabawa da salihai.

6. Allah ya riga ya tanadi wutar Jahannama ga masu shigar ta, ba sai nan gaba za a halicce ta ba, kamar yadda wasu suke faɗa.

Suratul Kahf (99-102)

*وَتَرَكۡنَا بَعۡضَهُمۡ يَوۡمَئِذٖ يَمُوجُ فِي بَعۡضٖۖ وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَجَمَعۡنَٰهُمۡ جَمۡعٗا ٩٩ وَعَرَضۡنَا جَهَنَّمَ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡكَٰفِرِينَ عَرۡضًا ١٠٠ ٱلَّذِينَ كَانَتۡ أَعۡيُنُهُمۡ فِي غِطَآءٍ عَن ذِكۡرِي وَكَانُواْ لَا يَسۡتَطِيعُونَ سَمۡعًا ١٠١ أَفَحَسِبَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَن يَتَّخِذُواْ عِبَادِي مِن دُونِيٓ أَوۡلِيَآءَۚ إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا جَهَنَّمَ لِلۡكَٰفِرِينَ نُزُلٗا ١٠٢

99. Kuma Muka bar sashinsu (mutane) a wannan rana yana cakuɗa da wani sashi; aka kuma busa ƙaho, sannan Muka tattara su gaba ɗaya.

100. Muka kuma bijiro da (wutar) Jahannama a wannan ranar ga kafirai (su gan ta) ƙuru-ƙuru.

101. (Su ne) waɗanda idanuwansu suka makance daga ambatona, suka kuma kasance ba sa iya jin (gaskiya).

102. Yanzu waɗanda suka kafirta suna tsammanin su riƙi wasu bayina ababen bauta ba Ni ba? Lalle Mun tanadi Jahannama ta zama masauki ga kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, zai bar mutane a wannan ranar suna cakuɗa da junansu. Wannan aya ta 99 za ta iya ɗaukar ma'anar cewa, ranar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ƙaddara fitowar Yajuju da Majuju bayan ganuwar nan ta fashe, za su fito da yawa suna gauraya da mutane, suna ta ɓarna a kan dukiyoyinsu da lalata musu kayansu. Wannan kuwa zai faru ne kafin tashin alƙiyama.
Ayar kuma za ta iya ɗaukar ma'anar cewa, ana nufin ranar alƙiyama da mutane da aljanu za su gauraya da juna wuri ɗaya. Don haka aka bayyana cewa, za a busa ƙaho sai duk matattu su tashi, Allah ya tattara su wuri guda na farkonsu da na ƙarshensu. Shi ya sa ya bayyana cewa, a lokacin ne zai bijiro da Jahannama

ga kafirai su gan ta da duk abin da yake cikinta na azaba kafin su shige ta don a ƙara musu baƙin ciki da damuwa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Za a zo da Jahannama a ranar alƙiyama ana janye da ita da linzami dubu saba'in, kowane linzami ɗaya mala'iku dubu saba'in ne suke jan sa." [Muslim #2842].

Sai kuma ya bayyana halin da kafirai suka kasance a cikinsa wanda ya jawo musu azabar Allah, watau sun makantar da idanunsu da gangan, sun ƙi ganin gaskiya balle su karɓe ta, sannan kuma ba sa iya sauraron gaskiya su yi aiki da ita.
Sai kuma ya bayyana cewa, yanzu kafirai za su yi tsammanin su riƙi wasu bayi na Allah su zama majiɓinta al'amarinsu ba Allah ba, suna zaton za su amfane su a ranar alƙiyama, su kare musu azabar Jahannama? Babu shakka wannan zato nasu aikin banza ne. Su sani tun da har sun kafirce wa Allah da manzanninsa sun aikata abin da zukatansu suka ƙawata musu, to lalle kuwa Allah ya tanadar musu Jahannama don ta zamo masauki gare su. Tir da wannan masauki kuwa idan ya zamanto wutar Jahannama ce.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayani a kan wasu masu ayyuka na ibadu tuƙuru ba tare da shiriya ta Allah da Manzonsa ba, suna zaton suna aikata abin kirki ne, alhalin ayyukansu a lalace suke. To kuma balle waɗanda sun san abin da suke aikatawar mummuna ne, yaushe kuma za su yi tsammanin samun wani kyakkyawan sakamako daga Allah?

2. Ba za a tsayar wa kafirai wani ma'auni ba a lahira, domin amfanin ma'aunin shi ne a auna ayyuka masu kyau da marasa kyau; a ga waɗanne ne suka fi rinjaye, to su kuwa ba su da ma wani aiki kyakkyawa da har za a auna shi, domin sharaɗin kyan aikin shi ne imani, su kuwa ba su da shi.

3. Tabbatar da awon ayyukan bayi a lahira.

4. Haɗarin yin izgili da ayoyin Allah da hadisan Manzonsa (ﷺ).

Suratul Kahf (103-106)

قُلْ هَلْ نُنَبِّئُكُم بِٱلْأَخْسَرِينَ أَعْمَٰلًا ﴿١٠٣﴾ ٱلَّذِينَ ضَلَّ سَعْيُهُمْ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَهُمْ يَحْسَبُونَ أَنَّهُمْ يُحْسِنُونَ صُنْعًا ﴿١٠٤﴾
أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ وَلِقَآئِهِۦ فَحَبِطَتْ أَعْمَٰلُهُمْ فَلَا نُقِيمُ لَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ وَزْنًا ﴿١٠٥﴾ ذَٰلِكَ جَزَآؤُهُمْ جَهَنَّمُ
بِمَا كَفَرُوا۟ وَٱتَّخَذُوٓا۟ ءَايَٰتِى وَرُسُلِى هُزُوًا ﴿١٠٦﴾

103. Ka ce (da su): "Ba na ba ku labarin waɗanda suka fi asarar ayyukansu ba?

104. "(Su ne) waɗanda aikinsu ya ɓace a rayuwarsu ta duniya alhali kuwa su suna tsammanin suna kyautata aiki ne."

105. Waɗannan (su ne) waɗanda suka kafirce wa ayoyin Ubangijinsu da kuma gamuwa da shi, sai ayyukansu suka lalace, ba za Mu sanya musu wani ma'auni ba a ranar alƙiyama.

106. Wannan shi ne sakamakonsu, Jahannama, saboda kafircewa da suka yi suka kuma riƙi ayoyina da manzannina abin yi wa izgili.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya ba wa kafirai labarin waɗanda suka fi kowa asarar ayyukansu, watau waɗanda suka yi wahalar banza ba tare da dacewa da wani sakamako ba a wurin Allah, da cewa, su ne waɗanda ayyukansu suka ɓace tun a nan duniya domin sun yi su ba bisa koyarwar Shari'a ba, amma su suna tsammanin suna kyautata aikinsu ne.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, su ne waɗanda suka kafirce wa ayoyin Allah masu tabbatar da Kaɗaitakarsa, suka kuma kafirce wa haɗuwa da shi ranar alƙiyama. Saboda haka ayyukansu suka rushe, Allah ya tabbatar musu da cewa, ba zai sanya musu wani ma'auni ba a ranar alƙiyama, kuma ko da an auna su ba za su yi nauyi a ma'auni ba.
Sannan ya bayyana dalilin irin wannan sakamako da ya yi musu da cewa, saboda sun kafirce wa Allah ne, sun kafirce wa ayoyinsa, kuma sun riƙi ayoyin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da manzanninsa abin yi wa izgili.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani da aiki na ƙwarai shi ne sababin shiga Aljanna.
2. Gidajen Aljanna hawa-hawa ne. Firdausi ita ce mafi zama ƙolin daraja a gidajen Aljanna.

3. Faɗin ilimin Allah da hikimominsa.

4. Annabi (ﷺ) mutum ne kamar sauran mutane, amma Allah ya zaɓe shi ya fifita shi a cikin sauran halittunsa.

5. Allah ba ya karɓar wani aiki na bawa sai ya cika sharuɗɗa biyu:
• **Na farko**, a gudanar da shi daidai da koyarwar Shari'a, watau ya dace da littafin Allah da sunnar Manzonsa (ﷺ).
• **Na biyu**, a yi shi don Allah ba don wani ba ko wata manufa ta duniya.
Duk aikin da ya rasa ɗaya daga cikin sharuɗɗan nan biyu, to ba karɓaɓɓe ne ba a wurin Allah, mai shi ba ya da wani lada da zai samu a kansa ranar alƙiyama, sai dai ya zame masa alhaki da za a kama shi da shi.
Sharaɗi na farko ya nuna duk wata ibada ta bidi'a ba za ta karɓu a wurin Allah ba. Sharaɗi na biyu ya nuna duk wani aiki na Shari'a da riya ta shige shi ba zai sami karɓuwa wurin Allah ba.

Suratul Kahf (107-110)

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ كَانَتۡ لَهُمۡ جَنَّٰتُ ٱلۡفِرۡدَوۡسِ نُزُلًا ١٠٧ خَٰلِدِينَ فِيهَا لَا يَبۡغُونَ عَنۡهَا حِوَلٗا ١٠٨ قُل لَّوۡ كَانَ ٱلۡبَحۡرُ مِدَادٗا لِّكَلِمَٰتِ رَبِّي لَنَفِدَ ٱلۡبَحۡرُ قَبۡلَ أَن تَنفَدَ كَلِمَٰتُ رَبِّي وَلَوۡ جِئۡنَا بِمِثۡلِهِۦ مَدَدٗا ١٠٩ قُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ فَمَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلۡيَعۡمَلۡ عَمَلٗا صَٰلِحٗا وَلَا يُشۡرِكۡ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدَۢا ١١٠

107. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari to Aljannar Firdausi ita ce ta kasance masaukinsu.

108. Suna masu dawwama a cikinta, ba sa neman wani musaya da ita.

109. Ka ce (da su): "Da kogi zai zamanto tawada don (rubuta) kalmomin Ubangijina, to lalle da kogin ya ƙare kafin kalmomin Ubangijina su ƙare, ko da kuwa Mun zo da ƙarin wasu (koguna) kamarsa.

110. Ka ce: "Ni dai mutum ne kawai kamarku da ake yi mini wahayi cewa abin bautarku abin bauta ne Ɗaya; don haka wanda ya kasance yana tsoron gamuwa da Ubangijinsa, to sai ya yi aiki nagari, kada kuma ya tara wani cikin bautar Ubangijinsa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rufe wannan Sura ne da yi wa muminai masu ayyuka na ƙwarai alƙawarin ba su gidajen Aljannar Firdausi a matsayin masaukinsu ranar alƙiyama.
Aljannar Firdausi ita ce ƙololuwar Aljanna kuma mafi daraja.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle a Aljanna akwai daraja ɗari waɗanda Allah ya tanade su don masu jihadi don ɗaukaka addininsa, tazarar da take tsakanin darajoji biyu kamar tazarar da ke tsakanin sama da ƙasa ne. Don haka idan za ku roƙi Allah Aljanna to ku roƙe shi Firdausi, domin ita ce mafi ɗaukakar Aljanna kuma mafi falalarta; daga cikinta ne ƙoramun Aljanna suke ɓuɓɓugowa." [Bukhari #2790 da Ahmad #8419].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, muminai za su dawwama a cikin wannan Aljannar har abada suna cikin ni'imomin Allah cikakku babu tawaya; ba za su taɓa neman wani musanya da ita ba, saboda ba za su taɓa ƙosawa da ita ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman lamarinsa da yalwar siffofinsa waɗanda sanin bayinsa ba zai iya kewaye su ba. Ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa musu cewa, da a ce za a mayar da ruwan kogi gaba ɗaya ya zama ruwan tawada, a kuma mayar da duk bishiyoyin duniya su zama alƙaluma domin a rubuce kalmomin Ubangiji na Ƙudurarsa da na iliminsa da hikimominsa, to da kogin ya ƙare duk yawansa kuwa ba tare da kalmomin Allah sun ƙare ba, ko da kuwa za a ƙara da wani kogin kamarsa.
Sai kuma ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya faɗa wa kafirai cewa, shi mutum ne kamarsu, watau ba mala'ika ne ba, ba kuma aljani ne ba, ba kuma wata halitta ta daban ba. To amma kuma shi Allah ya zaɓe shi ne yana yi masa wahayi cewa, abin bautarsu na gaskiya ɗaya ne ba shi da abokin tarayya, shi ne Allah.
To don haka, duk wanda yake jin tsoron haɗuwa da Ubangijinsa, to lalle ya yi aiki na ƙwarai wanda ya dace da Shari'a, kuma ya tsantsanta shi ga Allah shi kaɗai, kada kuma ya haɗa Ubangijinsa da kowa wajen bautarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zamantowar mutum bawan Allah, watau mai bauta gare shi tare da so da ƙanƙantar da kai, matsayi ne a wurin Allah da yakan jawo masa samun rahamarsa a duniya da lahira.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son bawansa ya roƙe shi yana mai ikhlasi cikin addu'arsa. Don haka Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fifita ya yi addu'arsa a ɓoye ba tare da wani ya sani ba.

3. Bawa ya bayyana rauninsa da gajiyawarsa yana daga cikin abin neman kusanci zuwa ga Allah, domin ya amsa masa addu'arsa.

4. Yana da kyau mai addu'a ya ambaci ni'imomin da Allah ya yi masa ya yi tawassuli watau ya nemi kusanci da shi da hakan.

5. Nuna damuwa da masalaha ta addini fiye da sauran maslahohi.

6. Annabawa suna barin gadon ilimin annabci ne ba na dukiya ba, shi ya sa Zakariyya ya roƙi Allah ya ba shi ɗa don ya gaji iliminsa da na zurriyyar gidan Annabi Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Wannan ya nuna ba gadon dukiya ne ba, domin gadon dukiyar zurriyyar Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) tana ga magadansu ne ba ɗan Zakariyya ba.

19-Suratu Maryam

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da sunan '*Suratu Maryam'*. Kuma wannan shi ne sunanta a cikin *Mus'hafai* da littattafan Tafsiri da na Hadisi. Abin da ya sa aka kira ta da wannan suna kuwa, saboda a cikinta an yi faffaɗar magana a kan ƙissar Maryamu, tare da batun ɗanta Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da kuma na danginta. A gabanin saukar da wannan Sura babu wata Sura da aka yi batun Nana Maryam da ɗanta Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kamar yadda aka yi a wannan Sura. Sai daga baya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi batunta a cikin *Suratu Ali Imran*.
A cikin wasu littattafan Hadisi an kira ta da sunan haruffanta na farko, watau () kamar yadda ya zo a cikin hadisin Ummu Salama wanda ya yi magana a kan hijirar Musulmi zuwa ƙasar Habasha, inda take cewa: "Sai Ja'afar ya karanta ()". [Ahmad #1740].

Abu Huraira da Ibn Abbas sun kira ta da haka. [Dubi, Musnad #8552 da Ibnu Hibban #7156 da Tafsirin Ibnu Ashur, Juzu'i na 8, shafi na 58].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wajen baki ɗayan malamai. Amma an rawaito daga Muƙatil ɗan Sulaiman ya ce: "Ayar sujjada, watau aya ta (58) *Madaniyya* ce".
Suyuɗi a cikin littafin "*Al-Itaƙaan*" ya hakaito cewa wani ya togace aya ta (71) ya ce *Madaniyya* ce, amma kuma bai ambaci sunansa ba. Magana dai ingantacciya ita ce wannan Surar gaba ɗayanta *Makkiyya* ce.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce sura ta arba'in da huɗu (44) a jerin saukar surori. An saukar da ita bayan *'Suratu Faɗir'* kafin '*Suratu `Ɗaha'*.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Makka da Madina ayoyinta tis'in da tara ne (99), amma a lissafin mutanen Sham da Kufa kuwa adadinsu tis'in da takwas ne (98). Wannan shi ne kuma abin da yake rubuce cikin *Mus'hafai*.

5. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Kaɗaita Allah da bauta tare da kore masa abokin tarayya, da kuma kore masa ɗa.
• Ta taɓo batun tashin alƙiyama, inda ta hasko wasu abubuwa da za su gudana a ranar.
• Tubalin ginin wannan Surar ƙissoshi ne waɗanda suka fara da ƙissar Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Yahya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sannan ƙissar Maryamu da haihuwar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sannan kuma wani ɓangare na ƙissar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifinsa. Sannan ta yi nuni zuwa ga wasu annabawa, kamar Annabi Musa da Annabi Is'haƙa da Annabi Isma'ila da Annabi Idris. A taƙaice ana iya cewa, kimanin biyu bisa ukunta (2/3) ƙissoshi ne.
• Ta yi nuni zuwa ga girman sha'anin Alƙur'ani.

• Cikin manya-manyan manufofin wannan Sura akwai tabbatar da yalwar rahamar Ubangiji, domin an ambaci "*Arrahman*" a cikinta har sau goma sha shida (16), wanda hakan ke tabbatar da cewa sunan Allah ne, kuma Rahama Siffarsa ce, don kuma wannan ya zama martani ga mushrikan Makka da suke cewa su ba su yarda da wannan suna ba.

Suratu Maryam (1-6)
كٓهيعٓصٓ ١ ذِكۡرُ رَحۡمَتِ رَبِّكَ عَبۡدَهُۥ زَكَرِيَّآ ٢ إِذۡ نَادَىٰ رَبَّهُۥ نِدَآءً خَفِيًّا ٣ قَالَ رَبِّ إِنِّي وَهَنَ ٱلۡعَظۡمُ مِنِّي وَٱشۡتَعَلَ ٱلرَّأۡسُ شَيۡبٗا وَلَمۡ أَكُنۢ بِدُعَآئِكَ رَبِّ شَقِيّٗا ٤ وَإِنِّي خِفۡتُ ٱلۡمَوَٰلِيَ مِن وَرَآءِي وَكَانَتِ ٱمۡرَأَتِي عَاقِرٗا فَهَبۡ لِي مِن لَّدُنكَ وَلِيّٗا ٥ يَرِثُنِي وَيَرِثُ مِنۡ ءَالِ يَعۡقُوبَۖ وَٱجۡعَلۡهُ رَبِّ رَضِيّٗا ٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. KAF HA YA AIN SAD

2. (Wannan) ambaton rahamar Ubangijinka ne (da Ya yi wa) Bawansa Zakariyya.

3. Lokacin da ya kira Ubangijinsa (ya roƙe Shi) cikin asiri.

4. Ya ce: "Ya Ubangiji lalle ƙasusuwana sun yi rauni, kaina kuma ya yi fari fat da furfura, Ubangijina ban kuma zama mai taɓewa ba game da roƙon Ka.

5. "Kuma lalle ni na ji tsoron dangina a bayana, matata kuma ga ta bakarara ce, saboda haka Ka yi mini baiwa daga gare Ka ta (ɗa) majiɓinci.

6. "(Wanda) zai gaje ni ya kuma gaji iyalan Ya'aƙub; Ubangijina kuma Ka sanya shi yardajje (a wurinka)."

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da wasu haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori da suka gabace ta. Mun riga mun ambaci bayanin malamai a kansu. [Dubi farkon *Suratul Baƙara*].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a nan yana ba da labarin bawansa ne Annabi Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) game da wata babbar rahama da ya yi masa ta samun haihuwa bayan ya tsufa tukuf bai haihu ba.
Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ɗaya ne daga cikin annabawan Banu Isra'ila, yana auren `yar'uwar Maryam mahaifiyar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

An karɓo daga Maliku ɗan Sa'asa'a (Allah ya ƙara masa yarda) a cikin dogon hadisinsa na bayanin Isra'in Annabi (ﷺ) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Sai Jibrilu ya hau da shi har suka iso sama ta biyu, sai ya nemi a buɗe ƙofa, sai aka ce masa: "Wane ne?" Sai ya ce: "Jibrilu ne." Sai aka ce masa: "Wane ne kuma tare da kai?" Sai ya ce: "Muhammadu ne." Sai aka ce: "Shin an aika masa ne?" Ya ce: "E." Ko da na shiga sai na ga Yahya da Isa kuma su biyun 'ya'yan mata zar suke..." [Dubi Bukhari #3430].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi addu'a cikin dare a ɓoye ya roƙi Allah ya ba shi ɗa. Ya nuna wa Ubangijinsa raunin jikinsa saboda tsufa, ga shi kuma furfura duk ta baibaye kansa, kuma ya tabbata ba zai rasa samun biyan buƙatarsa ta samun ɗa ba duk da halin da yake ciki.
Sai kuma ya bayyana dalilinsa na neman haihuwa a wannan yanayi, shi ne yana jin tsoron bayan mutuwarsa danginsa ba za su tsaya su kula da tafiyar da harkokin addini ba kamar yadda yake yi a matsayinsa na

Shugaban Limaman Banu Isra'ila a zamaninsa, domin ganin yadda suka shagaltar da kansu da harkokin neman abinci. Ya kuma bayyana cewa matarsa bakarara ce ba ta haihuwa; wannan ya sa yake ta roƙon Allah ya dube shi da rahamarsa ya ba shi ɗa wanda zai taimaka masa, wanda kuma zai gaji annabta da ilimi daga gare shi da kuma iyalan Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sannan ya roƙi Allah ya sanya shi ya zama yardadde a addininsa da halayensa da iliminsa a wajensa da wajen sauran jama'a.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yi wa mutum albishir da abin farin ciki kafin ya same shi.

2. Halaccin zaɓa wa yaro suna tun kafin a haife shi.

3. Zaɓa wa yaro sunan da ya dace, mai kyawun ma'ana.

4. Sa wa Yahya wannan suna wata bushara ce ga mahaifinsa cewa zai rayu har ma ya gaje shi kamar yadda ya roƙa a addu'arsa.

5. Halaccin neman ƙarin yaƙini da sakankancewa a kan abin da mutum ba ya shakkarsa, kamar yadda Zakariyya ya nemi alama ta samun abin da aka yi masa albishir da shi, duk kuwa da cewa ba ya shakkar gaskiyar lamarin.

Suratu Maryam (7-11)
يَٰزَكَرِيَّآ إِنَّا نُبَشِّرُكَ بِغُلَٰمٍ ٱسۡمُهُۥ يَحۡيَىٰ لَمۡ نَجۡعَل لَّهُۥ مِن قَبۡلُ سَمِيّٗا ٧ قَالَ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي غُلَٰمٞ وَكَانَتِ ٱمۡرَأَتِي عَاقِرٗا وَقَدۡ بَلَغۡتُ مِنَ ٱلۡكِبَرِ عِتِيّٗا ٨ قَالَ كَذَٰلِكَ قَالَ رَبُّكَ هُوَ عَلَيَّ هَيِّنٞ وَقَدۡ خَلَقۡتُكَ مِن قَبۡلُ وَلَمۡ تَكُ شَيۡـٔٗا ٩ قَالَ رَبِّ ٱجۡعَل لِّيٓ ءَايَةٗۚ قَالَ ءَايَتُكَ أَلَّا تُكَلِّمَ ٱلنَّاسَ ثَلَٰثَ لَيَالٖ سَوِيّٗا ١٠ فَخَرَجَ عَلَىٰ قَوۡمِهِۦ مِنَ ٱلۡمِحۡرَابِ فَأَوۡحَىٰٓ إِلَيۡهِمۡ أَن سَبِّحُواْ بُكۡرَةٗ وَعَشِيّٗا ١١

7. (Aka ce): Ya Zakariyya, lalle Muna yi maka albishir da samun ɗa, sunansa Yahya, ba Mu kuwa sanya wa wani sunan ba gabaninsa.

8. Ya ce: "Ubangijina ta ƙaƙa zan samu ɗa, alhali kuwa matata ta zamanto bakarara ce, ni kuma ga shi na tsufa tukuf".

9. Ya ce: "Kamar haka Ubangijinka Ya faɗa (cewa): 'Shi (wannan) mai sauƙi ne a wurina, don kuwa haƙiƙa Na halicce ka alhalin ba ka zama komai ba.'"

10. Ya ce: "Ubangijina Ka sanya mini wata alama." Sai (Allah) Ya ce: "Alamarka ita ce ka kasa yi wa mutane magana (tsawon) kwana uku daidai."

11. Sannan (Zakariyya) ya fito wa mutanensa daga wurin ibada ya yi musu ishara cewa: "Ku yi tasbihi safe da maraice."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya amsa addu'ar Annabi Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya kuma yi masa albishir da cewa, zai ba shi ɗa kuma sunansa Yahya, kuma babu wanda aka taɓa sa wa wannan suna gabaninsa.
Sai Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana mamakinsa da wannan babbar Ƙudura ta Allah; ta yaya zai sami haihuwa alhalin matarsa bakarara ce ba ta haihuwa, shi kuma ga shi ya tsufa tukuf

duk jikinsa ya yi rauni? Shin zai dawo masa da ƙarfinsa ne na jiki ya kuma mayar da matarsa mai haihuwa? Ko kuma wata matar zai aura su haihu da ita?!
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa cewa, yana sane da matarsa ba ta haihuwa kuma shi ya tsufa tukuf ya yi rauni. To amma duk wannan abu ne mai sauƙi a wurin Allah ya ba su ɗa cikin wannan hali. Ya kuma tuna masa cewa, a da shi fa babu shi kwata-kwata amma ya halicce shi; to don haka samar da ɗa daga miji tsoho da mata bakarara ya fi komai sauƙi a wurinsa.
Sai Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya buƙaci Allah ya nuna masa wata alama da zai ƙara nutsuwa da ita game da albishir da aka yi masa, wadda kuma za ta nuna masa ya kusa samun wannan albishir. Sai ya bayyana masa cewa alamar da zai gani ita ce, ba zai iya magana da mutane ba har tsawon kwana uku, ba kuma don wani ciwo ba, amma kuma zai iya yin zikiri da tsarkake Ubangijinsa.
Sai Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fito daga ɗakin ibadarsa zuwa ga mutanensa waɗanda suke jiran sa a wurin ibada domin ya jagorance su. Ya nuna musu da hannu cewa, su ci gaba da tsarkake Allah safe da yamma.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne mumini ya riƙe addininsa da ƙarfi a koyaushe.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hore wa Annabi Yahya siffofi na shugabanci:
Siffa ta farko, ilimi da fahimta.
Ta biyu, tausayin mutane da tausasa musu.
Ta uku, tsarkin zuciya da guje wa saɓa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Ta huɗu, kiyaye dokokin Allah tare da girmama shi.
Ta biyar, kyautata wa iyayensa domin fatan samun albarkar addu'o'insu.

3. Muhimmancin biyayya ga iyaye da kyautata musu a rayuwarsu da yi musu addu'a bayan sun bar duniya.

Suratu Maryam (12-15)
يَٰيَحۡيَىٰ خُذِ ٱلۡكِتَٰبَ بِقُوَّةٖۖ وَءَاتَيۡنَٰهُ ٱلۡحُكۡمَ صَبِيّٗا ١٢ وَحَنَانٗا مِّن لَّدُنَّا وَزَكَوٰةٗۖ وَكَانَ تَقِيّٗا ١٣ وَبَرَّۢا بِوَٰلِدَيۡهِ وَلَمۡ يَكُن جَبَّارًا عَصِيّٗا ١٤ وَسَلَٰمٌ عَلَيۡهِ يَوۡمَ وُلِدَ وَيَوۡمَ يَمُوتُ وَيَوۡمَ يُبۡعَثُ حَيّٗا ١٥

12. (Allah ya ce): "Ya Yahaya, ka riƙi littafin (Attaura) da ƙarfi"; Muka kuma ba shi annabci tun yana ƙarami.

13. Kuma (Muka hore masa) tausayi daga gare Mu da tsarkin (zuciya), ya kuma kasance mai kiyaye dokokin Allah ne.

14. Kuma mai biyayya ga mahaifansa, bai kuma zamanto mai taurin kai mai saɓa wa (umarnin Allah) ba.

15. Kuma aminci ya tabbata a gare shi ranar da aka haife shi da kuma ranar da zai mutu da kuma ranar da za a tashe shi rayayye.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa ya cika wa Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) burinsa, ya ba shi ɗa namiji, watau Yahya, ya raya shi har ya kai munzalin ba shi umarni, don haka ya kira shi ya umarce shi da ya riƙe littafin Attaura hannu biyu-biyu, ya kuma ba shi ilimi da fahimta da ƙoƙari tun yana yaro ƙarami. Ya kuma sanya shi mai tausayin mutane, ga shi kuma tsarkakakke daga aikata laifuka, kuma mai kiyaye dokokin Allah; yana aiki da umarninsa yana kuma guje wa haninsa. Ya

kuma sanya shi mai biyayya ne ga iyayensa yana tausaya musu tare da kyautatawa, sannan kuma ba mai saɓa wa umarnin Allah da na iyayensa ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa amincin Allah ya tabbata gare shi tun ranar da aka haife shi da ranar da zai mutu da kuma ranar alƙiyama da za a tashe shi da ransa. Waɗannan lokuta uku su ne waɗanda ɗan'adam ya fi samun kewa a cikinsu; to amma idan har ya sami aminci a cikinsu, wannan yana nuna sauran lokutansa ma zai aminta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Labarin haihuwar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fi na haihuwar Annabi Yahya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ban mamaki.

2. Bayan halittar ɗan'adam na farko da Allah ya yi ba tare da uwa da uba ba, babu wani abin mamaki kuma da ya kai na samar da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba tare da uba ba.

3. `Yan'adam ba su halarci lokacin halittar mutum na farko ba, sannan labarinsa ya shuɗe da jimawa, sai Allah ya ga damar ya nuna musu wani abin mamakin na biyu domin su ci gaba da ɗaukar darasi daga gare shi a kan cikar Ƙudurar Allah mai aikata abin da ya ga dama.

4. Ambaton labarin Maryamu a cikin Alƙur'ani yana nuna girman falalarta, domin zamantowarsa littafi da ake karanta shi a ko'ina a duniya, yana kuma ƙunshe da yabo da kyakkyawan ambatonta.

5. Halittar Annabi Isa ba tare da uba ba wata aya ce ga mutane mai nuna Ƙudurar mahaliccinsu wanda ya yi halitta iri daban-daban, kuma mai nuna cewa Allah yana iya zartar da kowane abu ba tare da samuwar sababinsa ba idan ya ga dama.

6. Aiko da manzo a cikin wata al'umma rahama ce gare su.

Suratu Maryam (16-21)
وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مَرۡيَمَ إِذِ ٱنتَبَذَتۡ مِنۡ أَهۡلِهَا مَكَانٗا شَرۡقِيّٗا ١٦ فَٱتَّخَذَتۡ مِن دُونِهِمۡ حِجَابٗا فَأَرۡسَلۡنَآ إِلَيۡهَا رُوحَنَا فَتَمَثَّلَ لَهَا بَشَرٗا سَوِيّٗا ١٧
قَالَتۡ إِنِّيٓ أَعُوذُ بِٱلرَّحۡمَٰنِ مِنكَ إِن كُنتَ تَقِيّٗا ١٨ قَالَ إِنَّمَآ أَنَا۠ رَسُولُ رَبِّكِ لِأَهَبَ لَكِ غُلَٰمٗا زَكِيّٗا ١٩ قَالَتۡ أَنَّىٰ يَكُونُ لِي غُلَٰمٞ وَلَمۡ يَمۡسَسۡنِي
بَشَرٞ وَلَمۡ أَكُ بَغِيّٗا ٢٠ قَالَ كَذَٰلِكِ قَالَ رَبُّكِ هُوَ عَلَيَّ هَيِّنٞ وَلِنَجۡعَلَهُۥٓ ءَايَةٗ لِّلنَّاسِ وَرَحۡمَةٗ مِّنَّاۚ وَكَانَ أَمۡرٗا مَّقۡضِيّٗا ٢١

16. Kuma ka ambaci (labarin) Maryamu a cikin (wannan) Littafi lokacin da ta ƙaurace wa mutanenta zuwa wani wuri a nahiyar gabas.

17. Sai ta saka shamaki tsakaninta da su (mutanen nata), to sai Muka aiko mata da Ruhinmu (shi ne Jibrilu) ya bayyana gare ta da surar daidaitaccen mutum.

18. Ta ce: "Lalle ina neman Allah ya tsare ni daga gare ka idan ka zamanto mai taƙawa ne."

19. Ya ce: "Ni manzo ne kawai na Ubangijinki na zo don in yi miki baiwar ɗa tsarkakakke."

20. Ta ce: "Ta ƙaƙa zan samu ɗa, alhalin kuwa wani namiji bai taɓa shafa ta ba, kuma ni ban zamanto mazinaciya ba?"

21. (Mala'ika) ya ce: "Kamar haka ne Ubangijinki Ya faɗa (cewa): "Shi (wannan) mai sauƙi ne a wurina, kuma don Mu mayar da shi aya ga mutane da kuma rahama daga gare Mu, kuma (yin haka) ya zamanto al'amari ne tabbatacce (rubuce a Lauhul-Mahafuzu)."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin haihuwar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba tare da uba ba.
Ya bayyana cewa mahaifiyarsa Maryam `yar Imrana ta ƙaurace wa `yan'uwanta zuwa nahiyar gabas da Baitul Maƙdis domin samun wurin ibada a keɓance ba tare da hayaniyar mutane ba, ba kuma tare da wani ya san abin da take yi ba, don ta samu sakewa da tsare mutuncinta.
Maryam ita ce `yar Imrana, ɗaya daga cikin limaman Banu Isra'ila a zamaninsa. Mahaifiyarta mace ce mai yawan bautar Allah da hidimar addini. Wannan ya sa ta roƙi Allah ya ba ta ɗa namiji domin ta sadaukar da shi don hidimta wa ɗakin ibada. To amma sai Allah ya ba ta `ya mace ita ce Maryam , sai ta yi wa Allah godiya, ta kuma cika alƙawarinta ta sadaukar da ita ga Allah lokacin da ta girma ta kai munzalin `ya mace. [Dubi, *Suratu Ali Imrana,* aya ta 32-42].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Maryamu ta sanya shamaki tsakaninta da mutanenta don kada su gan ta lokacin da take bautar Ubangijinta. Sai Allah ya aiko mata da Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cikin sura kyakkyawa ya bayyana gare ta, sai ta ji tsoron ko wani ne mai mugun nufi gare ta, sai ta nemi tsarin Allah daga sharrinsa kada ya cutar da ita, idan har shi mutum ne mai taƙawa da tsoron Allah. Sai Jibrilu ya fito ya bayyana mata cewa, shi ba mutum ba ne, shi mala'ika ne da Allah ya aiko shi don ya ba ta wani yaro mai tsarki.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Maryamu (() ta nuna tsananin mamaki da jin cewa za ta sami ɗa ba tare da tana da aure ba, ita kuma ba mai neman maza ba. Sai Jibrilu ya tabbatar mata da cewa, a hakan Allah zai ba ta ɗa, domin yin haka ya fi komai sauƙi a wajensa. Ya kuma bayyana mata hikimar da ta sa Ubangiji zai yi hakan, shi ne domin yaron ya zama wata shaida ce mai nuna cikar ikon Allah da Ƙudurarsa, kuma ya zama wata rahamar Allah ce ga mutanen da suka yi imani. Ya ƙara tabbatar mata da cewa, wannan halittar yaro da Allah zai yi wani hukunci ne da ya riga ya zartar da shi a littafin Lauhul Mahfuzu, don haka sai ya faru.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani bai fayyace tsawon lokacin da Maryam (() ta zauna ɗauke da cikin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba, amma mafi yawancin malaman tafsiri suna ganin ta ɗauki cikinsa ne wata tara kamar sauran mata. Wasu kuma suna ganin babu wata tazara tsakanin samun cikinta da haihuwarta.

2. Halaccin burin mutuwa lokacin tsoron faɗawa cikin wata fitina. Maryam ta yi burin ina ma a ce ta mutu saboda abubuwa biyu:
Na farko, ta guji a yi mata mummunan zato game da addininta, hakan ya jefa ta cikin wata fitina.
Na biyu, kada mutanenta su auka cikin haɗarin jifan marar laifi da zina, su halaka a dalilin haka.

3. Allah ya hore wa Maryamu abinci mai kyau da ruwan sha mai tsafta don ya zamanto wata babbar karama gare ta wadda kowa zai gani da idonsa, ya tabbata Allah ba zai yi mata irin wannan karramawa ba sai domin ita waliyyiyarsa ce.

4. Kazar-kazar wajen neman halal ba ya kore dogaro ga Allah. Ana so bawa ya taɓuka yin wani abu domin Allah ya taimake shi, kada ya zauna wuri guda ya ce arziƙinsa zai iske shi a duk inda yake.

Suratu Maryam (22-26)

۞فَحَمَلَتْهُ فَٱنتَبَذَتْ بِهِۦ مَكَانًا قَصِيًّا ﴿٢٢﴾ فَأَجَآءَهَا ٱلْمَخَاضُ إِلَىٰ جِذْعِ ٱلنَّخْلَةِ قَالَتْ يَٰلَيْتَنِى مِتُّ قَبْلَ هَٰذَا وَكُنتُ نَسْيًا مَّنسِيًّا ﴿٢٣﴾ فَنَادَىٰهَا مِن تَحْتِهَآ أَلَّا تَحْزَنِى قَدْ جَعَلَ رَبُّكِ تَحْتَكِ سَرِيًّا ﴿٢٤﴾ وَهُزِّىٓ إِلَيْكِ بِجِذْعِ ٱلنَّخْلَةِ تُسَٰقِطْ عَلَيْكِ رُطَبًا جَنِيًّا ﴿٢٥﴾ فَكُلِى وَٱشْرَبِى وَقَرِّى عَيْنًا ۖ فَإِمَّا تَرَيِنَّ مِنَ ٱلْبَشَرِ أَحَدًا فَقُولِىٓ إِنِّى نَذَرْتُ لِلرَّحْمَٰنِ صَوْمًا فَلَنْ أُكَلِّمَ ٱلْيَوْمَ إِنسِيًّا ﴿٢٦﴾

22. Sai ta ɗauki cikinsa sannan ta (tafi) da shi wani wuri mai nisa.

23. Sai ciwon naƙuda ya tilasta mata zuwa ga kututturen dabino, ta ce: "Ina ma na mutu tun kafin wannan (abu ya faru), na kuma kasance yasasshiya, mantacciya!"

24. Sai ya kira ta daga ƙarƙashinta cewa: "Kada ki yi baƙin ciki, haƙiƙa Ubangijinki Ya sanya ƙorama a ƙarƙashinki.

25. "Ki kuma girgiza kututturen dabinon nan zai zubo miki da lubiyar dabino nunanniya.

26. "Don haka ki ci, ki sha, kuma ki kwantar da hankalinki; kuma duk mutumin da kika gani (ya yi magana da ke), sai ki yi nuni da cewa: "Na ɗauki alƙawari ga Allah na kame bakina, ba zan yi magana da wani mutum ba yau."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, bayan Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi busa ga Maryamu (() ta ɗauki cikin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai ta ji tsoron abin kunyar da za ta faɗa cikinsa, sai ta tafi wani wuri mai nisa inda ba mai ganin ta. Yayin da lokacin haihuwarta ya zo sai ta nufi wurin wani kututturen busasshiyar itaciyar dabino, a nan ne ta ji duk abin duniya ya dame ta, ga zafin naƙuda, ga shi kuma ba abinci ko abin sha, sannan ga tunanin maganganun mutane idan sun gan ta da jariri. Waɗannan abubuwa su ne suka sanya ta burin ina ma a ce ta mutu kafin wannan lokaci, an daina maganarta kuma an daina tunawa da ita sam-sam. To a nan sai ta ji Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kirawo ta ta ƙarƙashin ƙafafunta cewa, kada ta yi baƙin ciki, Ubangijinta ya tanadi wata ƙorama ta ƙarƙashinta wadda ruwanta zai amfane ta wajen sha da harkokin haihuwa. Ya kuma umarce ta da ta girgiza kututturen busasshiyar itaciyar dabinon nan, za ta zubo mata da lubiyar nunannen dabino mai daɗi, wadda za ta ci ta kuma sha ruwan wannan ƙoramar. Ya kuma umarce ta da ta kwantar da hankalinta, ta yi farin ciki da ɗanta kamar kowace mace da ta sami haihuwar ɗanta lafiya.
Ta ɓangaren maganganun mutane kuwa, sai ya umarce ta da cewa, idan ta gamu da wani ya tambaye ta ina ta sami jariri, to ta nuna masa cewa ta ɗauki alƙawari ga Allah na kame bakinta, don haka babu wanda za ta yi magana da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fara da tabbatar da shi bawan Allah ne domin nan gaba mutanensa za su yi da'awar shi ɗan Allah ne. Akwai kuma wasu fa'idoji a cikin wannan kamar haka:
• **Fa'ida ta farko,** maganar da Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi yana cikin zanin jego tana daga cikin dalilan da suka sa wasu suka ɗauka shi ɗan Allah ne, don haka sai ya zamanto farkon abin da ya fara tabbatarwa shi bawan Allah ne.
• **Fa'ida ta biyu,** idan ya zamanto sun yarda shi mai gaskiya ne to buƙata ta tabbata, watau shi ba ɗan Allah ne ba, bawan Allah ne. Idan kuwa sun ce ƙarya ya faɗa to wannan ma ya tabbatar da cewa shi ba Allah ne ba, don Allah ba ya maganar ƙarya.

• **Fa'ida ta uku,** babban abin da ake tuhumar Maryamu da shi a lokacin shi ne laifin aikata zina, amma sai Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai yi wata magana a kan haka ba, sai ya fara da tabbatar da bautarsa ga Allah domin ya zamanto ishara a kan cewa kore wa Allah tuhumar yana da ɗa ta fi muhimmanci a kan kore laifin zina daga Maryamu .
• **Fa'ida ta huɗu,** kawar da tuhumar shirka da Allah tana tabbatar da kawar da tuhumar laifin zina daga Maryamu, domin kowa ya san Allah ba zai albarkaci mazinaciya da samun ɗa mai girman daraja irin wannan ba.

2. Yana daga cikin albarkar mutum ya zamanto mai koya wa mutane ayyuka na alheri.

3. Salla tana zama wajibi a kan duk wani balagagge mai hankali matuƙar yana raye, ko da yana rashin lafiyar da ba zai iya salla da gangar jikinsa ba ko an ɗaure masa hannaye da ƙafafu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya keɓe Annabi Isa a tsakanin sauran mutanen Banu Isra'ila ya yabe shi da biyayya ga iyayensa, saboda ƙarancin samun hakan a cikinsu.

5. Ya ambaci biyayya ga iyaye bayan ɗa'ar Allah domin nuni zuwa ga girman sha'anin biyayya gare su.

6. Wani daga cikin magabata yana cewa: Da wuya ka sami mai saɓa wa iyayensa sai ka gan shi mutum ne mai girman kai hasararre.

Suratu Maryam (27-33)
فَأَتَتْ بِهِۦ قَوْمَهَا تَحْمِلُهُۥ ۖ قَالُوا۟ يَٰمَرْيَمُ لَقَدْ جِئْتِ شَيْـًٔا فَرِيًّا ﴿٢٧﴾ يَٰٓأُخْتَ هَٰرُونَ مَا كَانَ أَبُوكِ ٱمْرَأَ سَوْءٍ وَمَا كَانَتْ أُمُّكِ بَغِيًّا ﴿٢٨﴾ فَأَشَارَتْ إِلَيْهِ ۖ قَالُوا۟ كَيْفَ نُكَلِّمُ مَن كَانَ فِى ٱلْمَهْدِ صَبِيًّا ﴿٢٩﴾ قَالَ إِنِّى عَبْدُ ٱللَّهِ ءَاتَىٰنِىَ ٱلْكِتَٰبَ وَجَعَلَنِى نَبِيًّا ﴿٣٠﴾ وَجَعَلَنِى مُبَارَكًا أَيْنَ مَا كُنتُ وَأَوْصَٰنِى بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱلزَّكَوٰةِ مَا دُمْتُ حَيًّا ﴿٣١﴾ وَبَرًّۢا بِوَٰلِدَتِى وَلَمْ يَجْعَلْنِى جَبَّارًا شَقِيًّا ﴿٣٢﴾ وَٱلسَّلَٰمُ عَلَىَّ يَوْمَ وُلِدتُّ وَيَوْمَ أَمُوتُ وَيَوْمَ أُبْعَثُ حَيًّا ﴿٣٣﴾

27. Sai ta zo wa mutanenta da shi tana ɗauke da shi; suka ce: "Ya Maryamu, haƙiƙa kin zo da babban abu!

28. "Ya ke 'yar'uwar Haruna, mahaifinki bai kasance lalataccen mutum ba, mahaifiyarki ma ba mazinaciya ba."

29. Sai ta nuna shi; (sai) suka ce: "Ta ƙaƙa za mu yi magana da wanda yake ɗan jariri cikin shimfiɗar jego?"

30. (Isa) ya ce (da su): "Lalle ni bawan Allah ne, Ya ba ni littafi Ya kuma sanya ni Annabi.

31. "Ya kuma sanya ni mai albarka a duk inda nake, kuma Ya umarce ni da yin salla da kuma ba da zakka matuƙar ina raye.

32. "Kuma mai biyayya ga mahaifiyata, bai kuma sanya ni mai girman kai mai saɓo ba.

33. "Amincin (Allah) kuma ya tabbata a gare ni ranar da aka haife ni da ranar da zan mutu da kuma ranar da za a tashe ni rayayye."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin Maryamu da cewa ta ɗauko Annabi Isa bayan haihuwarsa ta zo da shi wajen mutanenta, su kuma suna ganin ta ɗauke da jariri sai hankalinsu ya tashi, suka shiga zarginta da cewa lalle ta zo musu da wani lamari da babu mai amincewa da

shi, domin yaya za a yi mace ta haihu ba tare da ta sadu da ɗa namiji ba. Sai kuma suka jingina ta ga wani mutum mai ibada da kame kai a lokacin, ana kiran sa Haruna, wasu malamai sun ce ɗan'uwanta ne.

An karɓo daga Mughira ɗan Shu'uba (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya aike ni zuwa ga mutanen Najrana sai suka ce da ni: "Me za ka ce, ga shi a cikin littafinku kuna karanta cewa: "Ya `yar'uwar Haruna", alhalin Annabi Musa ya riga Annabi Isa zuwa da shekaru kaza da kaza?" Sai Mughira ya ce: "Sai na rasa me zan faɗa musu. Lokacin da na dawo wajen Manzon Allah (ﷺ) sai na faɗa masa abin da ya faru, sai ya ce: "Shin ba su sani ba ne cewa suna sanya wa `ya'yansu sunayen annabawansu da mutanen kirkin cikinsu waɗanda suka gabace su?" [Muslim #2135].

Suka kuma faɗa mata cewa, mahaifinta bai zama lalataccen mutum ba kuma mahaifiyarta ma ba a san ta da zina ba. Watau dai suna nufin a dangi ita ce farkon wadda ta fara irin wannan mummunar ɗabi'ar. Sai Maryamu ta nuna musu jaririn da ke tare da ita, tana nufin su yi magana da shi, zai fayyace musu gaskiyar abin da ya faru. Sai suka yi mamakin wannan lamari nata, suka ce ta yaya za su yi magana da jaririn da yake ƙunshe cikin zanin goyo?
Lokacin da suka faɗi haka sai Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fara yi musu magana, ya bayyana musu cewa, shi bawan Allah ne, kuma ya riga ya ƙaddara zai ba shi littafin Linjila wadda za su yi hukunci da ita, kuma zai ba shi annabta. Ya kuma mayar da shi mai albarka a duk inda yake a kuma kowane zamani, domin zai zamanto mai koya wa mutane ayyukan alheri yana hana su munanan ayyuka. Sannan duk wanda zai zauna da shi zai sami albarkarsa. Ya ƙara da cewa, Allah ya yi masa wasiyyar kula da salla wadda haƙƙi ne babba daga cikin haƙƙoƙin Ubangijinsa, da kula da zakka wadda ita kuma haƙƙi ne daga cikin haƙƙoƙin jama'a. Ya kuma yi masa wasiyya da ya zama mai biyayya ga mahaifiyarsa domin tana da babban haƙƙi a kansa, bai kuma yi shi mutum mai girman kai ga mutane ba, bai kuma zama marashin rabo duniya da lahira ba. Watau shi mutum ne mai saukin kai da tawali'u ga mutane mai babban rabo duniya da lahira.
Sannan ya nuna wata falalar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya yi masa ta tabbatar masa da aminci ranar da aka haife shi, Shaiɗan bai samu komai daga gare shi ba, da ranar da zai mutu Allah zai tsare shi daga duk wata azaba da kuma ranar alƙiyama lokacin da za a tashe shi a yi masa hisabi, Allah zai tsare shi daga shiga wuta.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wani ɗan'adam Shaiɗan yana shafar sa lokacin da mahaifiyarsa ta haife shi in ban da Maryamu da ɗanta." [Muslim #2366].

A wani lafazin ya ce: "Duk wani ɗan'adam da mahaifiyarsa za ta haife shi, Shaiɗan yana tsikarin sa, sai Maryamu da ɗanta."

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mutum uku ne kaɗai suka yi magana suna cikin zanin goyo: Isa ɗan Maryamu da sahibin Juraiju... da wani yaro wanda yake shan nonon mahaifiyarsa sai wani mutum ya zo wucewa ta gabansu yana haye a kan wata dabba ta alfarma sanye da kyawawan tufafi, sai mahaifiyar yaron nan ta ce: "Ya Allah ka sanya ɗana ya zama kamar wannan." Sai yaron ya saki nonon ya juya ya kalli mutumin sai ya ce: "Ya Allah kada ka sanya ni kamarsa", sai kuma ya ci gaba da shan nononsa. Sai kuma ga mutane sun zo wucewa suna dukan wata yarinya suna cewa, ta yi sata ta yi zina, ita kuma tana cewa: "*Hasbiyallahu wa ni'imal wakilu*." Sai mahaifiyar yaron nan ta ce: "Ya Allah kada ka sa ɗana shi ma ya zama kamar wannan." Sai yaron ya bar shan nonon ya ce: "Ya Allah ka sanya ni in zama kamarta." Sai uwar yaron nan ta yi mamaki. Sai yaron ya ce mata: "Wannan mutum na farko mutum ne mai girman kai, don haka na roƙi Allah kada ya sa in zama irinsa. Ita kuma wannan yarinya da suke cewa ta yi zina ta yi sata, sharri ne kawai mutane suke yi mata, ba ta yi zina ko sata ba, don haka na roƙi Allah ya sa in zama kamarta." [Bukhari #3436 da Muslim #2550].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Addinin Musulunci shi kaɗai ne a yau addini da ya yi bayanin haƙiƙanin wane ne Annabi Isa ba tare da wulaƙanta shi ba kamar yadda Yahudawa suka yi, ba kuma tare da zuguguta lamarinsa ba kamar yadda Nasara suka yi.

2. Tabbatar da Tauhidin Rububiyya yana lizimta tabbatar da Tauhidin Uluhiyya.

3. Hanya miƙaƙƙiya zuwa ga Allah ita ce kaɗai hanyar Musulunci, duk wata hanya wadda ba ita ba to karkatacciyar hanya ce, bin ta kuma ɓata ne.

Suratu Maryam (34-36)
ذَٰلِكَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَۚ قَوۡلَ ٱلۡحَقِّ ٱلَّذِي فِيهِ يَمۡتَرُونَ ٣٤ مَا كَانَ لِلَّهِ أَن يَتَّخِذَ مِن وَلَدٖۖ سُبۡحَٰنَهُۥٓۚ إِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرٗا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٣٥ وَإِنَّ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُوهُۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٣٦

34. Wannan shi ne Isa ɗan Maryamu. Zance na gaskiya wanda a kansa ne suke ta shakka suna jayayya (da junansu).

35. Ba zai yiwu a ce Allah yana da ɗa ba; tsarki ya tabbata a gare Shi. Idan Ya nufi zartar da wani lamari sai kawai Ya ce masa: ‘‘Kasance’’, sai ko ya kasance.

36. ‘‘Lalle kuma Allah shi ne Ubangijina kuma Ubangijinku, sai ku bauta masa. Wannan ita ce hanya madaidaiciya.’’

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Yahudu da Nasara cewa, wannan da aka ambaci yadda haihuwarsa ta kasance da kalamansa yana jariri shi ne gaskiyar magana game da Isa ɗan Maryamu (), ba kamar yadda Yahudu suke cin mutuncinsa ba suna cewa ɗan zina ne, ba kuma kamar yadda Nasara suke cewa shi ɗan Allah ne ba. Wannan ita ce maganar gaskiya wadda suka daɗe suna jayayya da shakku a kanta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tabbatarwa cewa ba zai yiwu ba a ce Allah yana da ɗa saboda shi mai cikakkiyar wadata ne ba shi da buƙatar komai, kuma kowa da komai mulkinsa ne kuma bayinsa ne. Ya tsarkaka daga duk wata tawaya ko aibi ko gajiyawa; kuma duk sa’adda ya nufi zartar da wani al’amari babba ko ƙarami sai dai kawai ya ce masa: ‘‘Kasance’’, sai abin ya tabbata. Don haka ne ma Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ƙara tabbatar wa al’ummarsa cewa, shi bawan Allah ne kuma Allah shi ne Ubangijinsa kuma Ubangijinsu wanda komai nasu yana hannunsa, don haka su bauta masa shi kaɗai; wannan ita ce hanya madaidaiciya mai sadar da bawa ga mahaliccinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mafi girman zalunci shi ne bawa ya yi da’awar Allah yana da abokin tarayya, to amma saboda girman haƙurin Ubangiji, yakan saurara wa bawa har sai ranar alƙiyama sannan ya kama shi da uƙubar laifinsa.

2. Kamar yadda shiriya take a bayyane, haka shi ma ɓata a bayyane yake, don haka ɓatacce ba shi da wani uzuri a wurin Ubangijinsa ranar alƙiyama.

3. Ranar alƙiyama ita ce ranar nadama; a cikinta ne Allah zai tara halittun farko da na ƙarshe a wuri ɗaya a yi musu tambayoyi game da ayyukansu; to wanda ya yi imani da Allah ya yi biyayya ga manzanninsa zai sami jin dadi na har abada. Wanda kuwa bai yi imani da Allah ba, bai bi manzanninsa ba, to zai shiga wahala ta har abada, ya yi hasarar kansa da iyalansa, a lokacin ne kuma zai yi nadama marar amfani, domin kuwa ba za ta canza komai ba.

Suratu Maryam (37-40)

فَٱخۡتَلَفَ ٱلۡأَحۡزَابُ مِنۢ بَيۡنِهِمۡۖ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن مَّشۡهَدِ يَوۡمٍ عَظِيمٍ ٣٧ أَسۡمِعۡ بِهِمۡ وَأَبۡصِرۡ يَوۡمَ يَأۡتُونَنَا لَٰكِنِ ٱلظَّٰلِمُونَ ٱلۡيَوۡمَ فِي
ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٣٨ وَأَنذِرۡهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡحَسۡرَةِ إِذۡ قُضِيَ ٱلۡأَمۡرُ وَهُمۡ فِي غَفۡلَةٖ وَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ٣٩ إِنَّا نَحۡنُ نَرِثُ ٱلۡأَرۡضَ وَمَنۡ عَلَيۡهَا وَإِلَيۡنَا يُرۡجَعُونَ ٤٠

37. Sai ƙungiyoyin suka sassaɓa a tsakaninsu; to bone ya tabbata ga waɗanda suka kafirta daga halartar rana mai girma (ita ce alƙiyama).

38. Ka yi mamakin jinsu da ganinsu a ranar da za su zo mana; sai dai azzalumai a wannan rana suna cikin ɓata mabayyani.

39. Ka kuma gargaɗe su game da ranar nadama, lokacin da aka ƙare hisabi, alhali kuwa su (a duniya) suna cikin rafkana kuma su ba sa yin imani.

40. Lalle Mu ne za Mu gaje ƙasa da wanda yake bayanta kuma gare Mu ne za a komar da su.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, an samu saɓani tsakanin ƙungiyoyi daban-daban game da lamarin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), wasu suka wuce gona da iri game da shi, wasu kuma suka ƙasƙantar da shi. Nasara ne suka wuce gona da iri kan batunsa, wasu suka ce ɗan Allah ne, wasu kuma suka ce da shi ɗayan uku ne, watau akwai Allah da ɗansa da kuma ruhi mai tsarki; wasu ma suka ce shi ne Allah. Yahudawa kuwa zagin sa suke yi, suna jifan mahaifiyarsa da aikata zina. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, duk waɗannan maganganun ƙarya ne kuma kafirci ne. Sannan ya yi gargaɗi mai tsanani ga kafirai masu wancan saɓani a kan Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa azaba mai tsanani ta tabbata gare su a ranar alƙiyama, ranar da kowa zai halarce ta, na farko da na ƙarshe, rana mai cike da manya-manyan ababen tsoro da azaba iri-iri.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Yahudawa sun karkasu ƙungiya saba'in da ɗaya ko da biyu; Nasara su ma sun karkasu ƙungiya saba'in da ɗaya ko da biyu; al'ummata kuwa za su karkasu ƙungiyoyi saba'in da uku." [Abu Dawud #4596 da Tirmizi #2640 da Ibn Majah #3991].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai za su zama masu ji da ganin gaskiyar da manzanni suka yi ta faɗa musu ita a duniya suna ƙaryata su, ji da gani na mamaki, a lokacin da hakan ba zai yi musu amfanin komai ba, domin sun kasance a nan duniya suna cikin ɓata mabayyani har suka riƙa ganin Allah yana da ɗa ko ɗayan uku ne, suka riƙa ƙaryata gaskiyar da aka zo musu da ita.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya gargaɗi azzalumai game da ranar alƙiyama, ranar da wasu da dama za su yi nadama a kan miyagun ayyukansu, su ma wasu mutanen kirki su yi nadama a kan rashin yawaita ayyukansu na alheri a duniya, domin a ranar an riga an rufe duk takardun ayyuka da abin da ke cikinsu mai kyau da mummuna, an yi wa kowa hisabi, 'yan Aljanna sun tafi Aljanna,

‘yan wuta ma sun tafi wuta. Amma kuma ga shi a nan duniya kafirai suna cikin rafkanuwa kuma ba sa ma yin imani da gaskiyar da ake faɗa musu game da ranar alƙiyama.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, shi ne kaɗai dawwamamme kowa zai halaka ya bar duniyar nan da abin da ke cikinta, Allah shi kaɗai ne zai gaje ta da duk abin da ta ƙunsa, kuma zuwa gare shi kowa zai koma.

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan ‘yan Aljanna suka shiga Aljanna, ‘yan wuta suka shiga wuta, za a zo da mutuwa a surar ƙosasshen rago, sai a tsayar da shi tsakanin Aljanna da wuta, sai a ce: “Ya ku ‘yan Aljanna, kun san wannan?” Sai su leƙo su ce: “E, wannan mutuwa ce.” Sai kuma a ce: “Ya ku ‘yan wuta, kun san wannan?” Sai su leƙo su kalle shi su ce: “E, wannan mutuwa ce.” Sai a ba da umarni a yanka shi, sai kuma a ce: “Ya ku ‘yan Aljanna, ku dawwama babu mutuwa. Ya ku ‘yan wuta, ku ma ku dawwama babu mutuwa.” Sannan sai Manzon Allah (ﷺ) ya karanta faɗar Allah: “Ka kuma gargaɗe su game da ranar nadama, lokacin da aka ƙare hisabi, alhali kuwa (a duniya) suna cikin gafala.” Sai ya yi nuni da hannunsa ya ce: “`Yan duniya suna cikin gafalar duniya.” [Bukhari #4730 da Muslim #4849].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin Annabi Muhammadu (ﷺ) game da halayyar da kafirai suke nuna masa na ƙiyayya da bijirewa ta hanyar nuna masa cewa kakansa ma Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gamu da irin wannan amma ya yi haƙuri, don haka shi ma ya yi haƙuri.

2. Ambaton labarin Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a cikin Alƙur’ani yana nuna girman falalarsa; domin Alƙur’ani shi ne mafi girman littafi da Allah ya saukar a bayan ƙasa, kuma duk labaran da ya ƙunsa na gaskiya ne babu wani kokwanto a cikinsu.

3. An siffanta Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa shi mai yawan gaskiya ne, domin ya kai ƙololuwa wajen rungumar umarnin Allah hannu biyu-biyu da gaskata shi da aiwatar da shi ba tare da inda-inda ba, kamar yadda ya kasance lokacin da Allah ya umarce shi da ya yanka ɗansa Annabi Isma’ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

4. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna wa mahaifinsa munin bautar gumaka, inda ya tabbatar masa da cewa bauta musu wani abu ne da ya saɓa wa aikin lafiyayyen hankali, domin kuwa babu mai cikakken hankalin da zai yarda ya bauta wa wani nakasasshen abu kamar gunki wanda ba ya iya yin komai, ba ya iya ganin komai, kuma ba zai iya maganta wa wani komai ba. Ashe bai dace mai hankali ya bauta wa irin wannan wulaƙantaccen abu ba. Da wannan ne ya tabbatar masa da cewa, Allah kaɗai shi ne ya dace a bauta wa domin shi ne kammalalle ta kowace fuska.

5. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna matuƙar girmamawa ga mahaifinsa da cikakken ladabi lokacin da yake ƙoƙarin ceto shi daga halakar bautar gumaka. Bai ce masa: “Baba ni mai ilimi ne kai kuma jahili ne” ba, ko ya ce masa: “Kai ba ka san komai ba ni ne na sani.” A’a, sai ya yi amfani da kalma mai taushi ya nuna masa wani ilimi ne ya zo masa wanda shi bai zo masa ba.

6. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya buƙaci ya yi wa mahaifinsa bayani a kan ilimin da ke tare da shi wanda shi babu irinsa a wurinsa, domin a al’ada ta manyan mutane ba kasafai suke rusuna wa mai ƙarancin shekaru a kan abin da ya shafi ilimin addini ba. Don haka ya tabbatar masa da wannan, domin ya kasance biyayyar da ke tsakaninsu ta ilimi ce ba ta shekaru ba.

7. Hakanan cikin hikima da girmamawa da ladabi Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna wa mahaifinsa cewa, abin da yake yi na bautar gumaka bauta ce ga Shaiɗan wanda kowa ya san ba alheri ko kaɗan tare da shi.

Suratu Maryam (41-45)

وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ إِبۡرَٰهِيمَۚ إِنَّهُۥ كَانَ صِدِّيقٗا نَّبِيًّا ٤١ إِذۡ قَالَ لِأَبِيهِ يَٰٓأَبَتِ لِمَ تَعۡبُدُ مَا لَا يَسۡمَعُ وَلَا يُبۡصِرُ وَلَا يُغۡنِي عَنكَ شَيۡـٔٗا ٤٢ يَٰٓأَبَتِ إِنِّي قَدۡ جَآءَنِي مِنَ ٱلۡعِلۡمِ مَا لَمۡ يَأۡتِكَ فَٱتَّبِعۡنِيٓ أَهۡدِكَ صِرَٰطٗا سَوِيّٗا ٤٣ يَٰٓأَبَتِ لَا تَعۡبُدِ ٱلشَّيۡطَٰنَۖ إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ كَانَ لِلرَّحۡمَٰنِ عَصِيّٗا ٤٤ يَٰٓأَبَتِ إِنِّيٓ أَخَافُ أَن يَمَسَّكَ عَذَابٞ مِّنَ ٱلرَّحۡمَٰنِ فَتَكُونَ لِلشَّيۡطَٰنِ وَلِيّٗا ٤٥

41. Kuma ka ambaci (labarin) Ibrahimu a cikin (wannan) littafi (Alƙur'ani). Lalle shi mutum ne mai yawan gaskiya (kuma) Annabi.

42. Lokacin da ya ce da Babansa: "Ya Babana, me ya sa kake bauta wa abin da ba ya ji ba kuma ya gani, kuma ba ya yi maka maganin komai?

43. "Ya Babana, Lalle ni haƙiƙa wani ilimi ya zo mini wanda kai bai zo maka ba, to ka bi ni zan shiryar da kai hanya madaidaiciya.

44. "Ya Babana, kada ka bauta wa Shaiɗan ; lalle Shaiɗan ya kasance mai saɓo ne ga (Allah) Mai rahama.

45. "Ya Babana, lalle ni fa ina tsoron azaba ta shafe ka daga (Allah) Mai rahama, sai ka zama majiɓincin Shaiɗan."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzon Allah (ﷺ) cewa, ya bai wa mutanensa labarin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), waɗanda suke cika bakin cewa su suna bin addininsa ne kuma su zurriyyarsa ne. To ya faɗa musu labarinsa da yadda ya fito ƙarara ya yaƙi bautar gumaka, ya yi kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, domin shi Annabi ne mai yawan gaskiya da aiki da ita.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Annabi Ibrahimu ya fito fili ya faɗa wa mahaifinsa Ãzara wanda yake bautar gumaka da ya sassaƙa da hannunsa kamar sauran mutanensa cewa, me ya sa zai riƙa bauta musu alhali ya tabbatar cewa gunki ba ya ji kuma ba ya gani ba kuma zai iya kare masa wata cuta ba, ko ya amfane shi da wani abu? Watau ya nuna masa cewa shi kansa ya fi gunkin da yake bauta wa, domin shi yana ji yana gani, kuma ya san abin da zai cuce shi ko ya amfane shi, to don me zai mayar da kansa ƙasa yana bauta wa wani ƙaskantacce?
Ya sake kiran mahaifinsa cikin girmamawa da ladabi ya tabbatar masa cewa, duk da cewa shi ɗansa ne da ya haifa to amma yanzu yana da wani ilimi na sanin Allah mahalicci wanda shi ba ya da shi, don haka ya bi shi zai nuna masa hanya madaidaiciya wadda za ta kai shi ga samun biyan buƙatarsa, ta tserar da shi daga abin da yake ƙi.
Ya sake kiran babansa cikin girmamawa yana hana shi bautar Shaiɗan ta hanyar yi masa biyayya. Ya nuna masa cewa, Shaiɗan ya kasance mai yawan saɓa wa Allah ne mai rahama; tun lokacin da ya umarce shi ya yi wa Adamu sujjada amma ya ƙi ya yi masa. Ya kuma fito ƙarara ya nuna wa mahaifinsa cewa yana jiye masa tsoron azabar Allah, idan har bai tuba ba ya bar wannan ɓata da yake kai, domin idan har ya yarda ya mutu a kansa to za a tashe shi tare da Shaiɗan, a kuma haɗa su wuri guda a cikin azaba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kalaman mahaifin Annabi Ibrahim sun nuna shi mutum ne mai zafi da kaushin mu'amala.

2. Mahaifin Annabi Ibrahimu mutum ne mai alfahari da gumakansa, yana matuƙar girmama su, don haka ya zaɓi rabuwa da ɗansa a kan ya ci gaba da sauraron maganganunsa a kan gumakansa.

3. Ɗabi'ar mumini ita ce tausasa magana ga jahilai ko da kuwa sun yi wauta da jahilci.

4. Ba ya halatta Musulmi ya nema wa kafiri gafarar Allah bayan ya mutu. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ma alƙawari ne ya yi wa mahaifinsa zai roƙa masa gafara, daga baya Allah ya hana shi ci gaba da hakan.

5. Halaccin mumini ya ƙaurace wa wurin da ba za a ƙyale shi ya bauta wa Allah ba, ya koma inda ya fi aminci a bayan ƙasa don ci gaba da bautar Allah.

Suratu Maryam (46-48)

قَالَ أَرَاغِبٌ أَنتَ عَنْ ءَالِهَتِي يَـٰٓإِبْرَٰهِيمُ ۖ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ لَأَرْجُمَنَّكَ ۖ وَٱهْجُرْنِي مَلِيًّا ﴿٤٦﴾ قَالَ سَلَٰمٌ عَلَيْكَ ۖ سَأَسْتَغْفِرُ لَكَ رَبِّيٓ ۖ إِنَّهُۥ كَانَ بِي حَفِيًّا ﴿٤٧﴾
وَأَعْتَزِلُكُمْ وَمَا تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَأَدْعُوا۟ رَبِّي عَسَىٰٓ أَلَّآ أَكُونَ بِدُعَآءِ رَبِّي شَقِيًّا ﴿٤٨﴾

46. (Babansa) ya ce: "Yanzu Ibrahimu ƙyamar iyayen gijina kake yi? To tabbas idan ba ka bari ba lalle zan jefe ka; ka ɓace min da gani na tsawon lokaci!"

47. (Annabi Ibrahimu) ya ce: "Aminci ya tabbata gare ka; zan nema maka gafarar Ubangijina; don ko lalle Shi ya tabbata Mai haba-haba ne da ni.

48. "Zan kuwa ƙaurace muku ku da abin da kuke bauta wa wanda ba Allah ba, in kuma roƙi Ubangijina, na kuma sa tsammanin cewa ba zan zama taɓaɓɓe ba game da roƙon Ubangijina."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda Ãzara mahaifin Annabi Ibrahimu ya mayar masa da martani cikin kakkausan lafazi, ya nuna mamakinsa game da yadda Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake ƙyamar bautar gumaka, har ya gargaɗe shi da cewa, idan bai yi watsi da waɗannan maganganun nasa ba to zai jefe shi har lahira, ko kuma in ba haka ba ya ɓace masa da gani, kada ya sake zuwa inda yake ballantana ya sake yi masa irin wannan wa'azin.
Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) dai ya ci gaba da bin hanya ta lalama da tausasa harshe ga mahaifinsa yayin da ya ga yadda ya fusata, ya nuna masa zai rabu da shi rabuwa ta mutunci ba tare da ya cutar da shi ba ko ya yi masa abin da bai dace ɗa ya yi wa mahaifinsa ba, har ma ya yi masa alƙawarin zai nema masa gafarar Allah da shiriya, domin ya tabbatar da cewa Allah mai tausaya masa ne matuƙa.
Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ɗauki lokaci yana nema wa mahaifinsa gafarar Allah, har lokacin ma da ya yi hijira zuwa Sham ya gina Ka'aba tare da ɗansa Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), a nan ma ya yi addu'a ga mahaifansa su biyu, kamar yadda ya zo a cikin *Suratu Ibrahim* aya ta 41.
To bayan ya gane cewa mahaifinsa ba zai shiriya ba, zai mutu ne yana gaba da Allah da addininsa, sai ya nesanta kansa da shi ya daina yi masa addu'ar neman gafara, kamar yadda ya zo cikin *Suratut Tauba,* aya ta 114.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin da Annabi Ibrahimu ya fitar da rai daga imanin mahaifinsa da mutanensa sai ya shelanta musu cewa, zai ƙaurace musu har da abubuwan da suke bauta wa ba Allah ba, zai koma inda zai samu damar bauta wa Allah shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba, ya yi kuma fatan cewa Allah ba zai hana masa duk abin da ya roƙe shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya bar wani abu da yake ƙauna saboda Allah, to Allah zai musanya masa da wanda ya fi shi alheri.

2. Samun zurriyya ta gari babbar kyauta ce daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Ba a ambaci Annabi Isma'ila a nan ba saboda ana batun kyautar da Allah ya yi wa Annabi Ibrahimu ne bayan barin mutanensa shi da matarsa Saratu wadda suka yi ƙaura tare. Sai kawai aka ambaci kyautar da ta haɗa su, su duka biyun, watau samun haihuwar Annabi Is'haƙa bayan sun fitar da rai saboda tsufa. Sannan kuma Annabi Is'haƙa shi ne wanda ya zauna tare da mahaifinsa Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a wuri guda ya riƙa ɗebe masa kewa, yayin da shi Annabi Isma'ila kuwa yana can nesa da shi a garin Makka tare da mahaifiyarsa Hajara.

Suratu Maryam (49-50)
فَلَمَّا ٱعۡتَزَلَهُمۡ وَمَا يَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَهَبۡنَا لَهُۥٓ إِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَۖ وَكُلّٗا جَعَلۡنَا نَبِيّٗا ٤٩ وَوَهَبۡنَا لَهُم مِّن رَّحۡمَتِنَا وَجَعَلۡنَا لَهُمۡ لِسَانَ صِدۡقٍ عَلِيّٗا ٥٠

49. To lokacin da ya ƙaurace musu tare da abin da suke bauta wa wanda ba Allah ba, sai Muka yi masa baiwa da Is'haƙa da Ya'aƙubu; kowannensu kuma Muka ba shi annabta.
50. Muka kuma yi musu baiwa da rahamarmu, kuma Muka sanya musu kyakkyawan ambato maɗaukaki.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Ibrahimu ya cika ƙudurinsa na ƙaurace wa babansa da mutanensa da abin da suke bauta wa ba Allah ba, ya koma inda ya ci gaba da ibada da roƙon Allah, sai ko Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa baiwar samun ɗa namiji tare da matarsa Saratu wanda suka sa wa suna Is'haƙa; shi ma kuma ɗan nasu ya sami ɗa a lokacin rayuwarsa, aka sa masa suna Ya'aƙubu. Dukkansu kuma Allah ya ba su annabta a lokacin rayuwar Annabi Ibrahim, don su zama masu ɗebe masa kewar rabuwa da mahaifinsa da mutanensa da ya yi. Sannan kuma Allah ya bayyana cewa ya yi musu baiwa ta alheri mai yawa tare da annabci, ya sa suka zamanto ababen yabo mai ɗorewa a gun kowa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman matsayin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni a ambaci labarinsa a cikin mafi girman littafi da ya saukar, watau Alƙur'ani.

2. Darajar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da zaɓinsa da ya yi har ya yi magana da shi, saboda haka ake ce masa "*Kalimul-lahi*".

3. Tabbatar wa da Allah magana da murya da ake jiyo ta, saboda kira da ganawa suna kasancewa ta hanyar sauraron muryar mai kiran ko abokin ganawar.

4. Annabcin Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya samo asali ne daga annabcin Annabi Musa, domin shi ne ya roƙa masa, kuma Allah ya karɓi roƙonsa. Wannan yana daga cikin babban ihsani da Musa ya yi wa ɗan'uwansa Haruna.

Suratu Maryam (51-53)
وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مُوسَىٰٓۚ إِنَّهُۥ كَانَ مُخۡلَصٗا وَكَانَ رَسُولٗا نَّبِيّٗا ٥١ وَنَٰدَيۡنَٰهُ مِن جَانِبِ ٱلطُّورِ ٱلۡأَيۡمَنِ وَقَرَّبۡنَٰهُ نَجِيّٗا ٥٢ وَوَهَبۡنَا لَهُۥ مِن رَّحۡمَتِنَآ أَخَاهُ هَٰرُونَ نَبِيّٗا ٥٣

51. Ka kuma ambaci (labarin) Musa cikin (wannan) Littafi (Alƙur'ani). Lalle shi zaɓaɓɓe ne, ya kuma kasance Annabi ne Manzo.

52. Muka kuma kira shi a gefen dutsen Ɗuri na dama, Muka kuma kusanto shi yana mai ganawa (da Mu).

53. Kuma cikin rahamarmu Muka yi masa baiwa da ɗan'uwansa Haruna (shi ma) Annabi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya ba da labarin Annabi Musa ɗan Imrana a cikin Alƙur'ani mai girma saboda girman darajarsa da babban matsayi da Allah ya ba shi, saboda ya zaɓe shi ya kuma ba shi annabta da manzanci zuwa Banu Isra'ila.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin babban matsayin da ya yi wa Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), shi ne lokacin da ya kirawo shi ta ɓangaren dama na dutsen Ɗuri a saharar Sina'i, ya kusanto da shi gare shi ya kuma gana da shi, a inda ya ji sautin Ubangijinsa. A nan ne kuma ya ba shi allunan Attaura a rubuce don ya karantar da al'ummarsa Banu Isra'ila. Sannan kuma ya yi masa wata baiwar daga cikin rahamarsa ya ba shi ɗan'uwansa Haruna a matsayin wazirinsa wanda zai taimaka masa wajen isar da saƙonsa yayin da shi Musa ɗin ya roƙi haka wajen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya kuma ba Haruna shi ma annabci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman darajar Annabi Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni a ambaci labarinsa a mafi girman littafi da ya saukar, watau Alƙur'ani.

2. An keɓance Isma'ila da ambato a nan shi kaɗai bayan an ambaci Ibrahimu da ɗansa Is'haƙa; domin shi Isma'ila shi ya fara zama kaka ga wata babbar al'umma, watau Larabawa tun gabanin Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zama kaka ga wata al'umma, watau Banu Isra'ila. Sannan kuma shi ne babban ɗan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya taya shi ginin ɗakin Ka'aba da umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. An yaba masa da cika alƙawari domin ya shahara da haka; bai taɓa yi wa Ubangijinsa alƙawarin zai yi wata ibada ba face sai ya cika wannan alƙawarin da ya yi, kamar yadda Ibnu Juraij yake faɗa.

4. Cika alƙawari wata ɗabi'a ce mai kyau da ya kamata kowane Musulmi ya siffantu da ita, domin karya alƙawari ɗaya ne daga cikin siffofin munafukai.

5. Allah ya aiko Annabi Isma'ila a matsayin Annabi kuma Manzo zuwa ga mutanensa waɗanda a wannan lokacin su ne iyalansa da mahaifiyarsa Hajara da 'ya'yansa da surukansa, watau ƙabilar Jurhum.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna fifikon Annabi Ismaila a kan ɗan'uwansa Annabi Is'haƙa yayin da ya siffanta shi da Annabci da Manzanci gaba ɗaya; shi kuma Is'haƙa ya siffanta shi da Annabci kaɗai, duk kuwa da cewa shi ma Manzo ne.

7. Wajibi ne a kan kowane Musulmi ya zamanto mai umartar iyalansa da ayyukan ɗa'a ga Allah, musamman tsayar da salla, domin girman sha'aninta bayan Kalmar Shahada.

Suratu Maryam (54-55)

وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ إِسۡمَٰعِيلَۚ إِنَّهُۥ كَانَ صَادِقَ ٱلۡوَعۡدِ وَكَانَ رَسُولٗا نَّبِيّٗا ٥٤ وَكَانَ يَأۡمُرُ أَهۡلَهُۥ بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱلزَّكَوٰةِ وَكَانَ عِندَ رَبِّهِۦ مَرۡضِيّٗا ٥٥

54. Kuma ka ambaci (labarin) Isma'ila a cikin (wannan) Littafi (Alƙur'ani). Lalle shi ya kasance mai gaskiyar alƙawari ne, kuma ya kasance Annabi ne, Manzo.

55. Kuma ya zamanto yana umartar iyalinsa da (tsai da) salla da kuma (ba da) zakka, kuma shi yardajje ne a wurin Ubangijinsa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ba da labarin Annabi Isma'ila ɗan Annabi Ibrahimu kuma kakan Shugaban `yan'adam (ﷺ). Allah ya yabe shi da cewa shi mutum ne da yake cika duk wani alƙawari da ya ɗauka, ko dai alƙawarin da yake tsakaninsa da Ubangijinsa ko kuma wanda ya yi da mutane, kamar alƙawarin da ya yi wa mahaifinsa Ibrahim na cewa zai same shi mai haƙuri da miƙa wuya lokacin da aka umarci mahaifin nasa da ya yanka shi, kuma ya cika masa wannan alƙawarin ya miƙa kansa gare shi kafin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fanshe shi da rago mai girma.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ya ba wa Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) annabci da manzanci, wannan kuwa ita ce babbar baiwar da Allah zai yi wa bawansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa yana tsayar da umarnin Allah cikin iyalansa, yana umartar su da yin salla wadda ta ƙunshi tsarkake bauta ga Allah shi kaɗai, yana kuma umartar su da ba da zakka wadda ta ƙunshi kyautata wa bayin Allah. Don haka shi Isma'ila ya zamanto yana taimakon kansa ya kuma taimaka wa wasu, musamman iyalansa waɗanda sun fi kowa cancantar da'awarsa da koyarwarsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku umarci 'ya'yanku da salla tun suna da shekara bakwai, ku kuma doke su a kanta idan sun kai shekara goma, kuma ku raba musu makwanci (watau tsakanin maza da mata)." [Ahmad #6756 da Abu Dawud #495].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi Isma'ila ya kasance yardajje a wurinsa, soboda ya zamanto mai neman yardarsa ne koyaushe, yana kuma aiki da umarninsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Darajar Annabi Idris (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Allah ya yi umarni a ambaci labarinsa a cikin littafin da ya fi kowanne littafi ɗaukaka.

2. Allah ya ɗaukaka Annabi Idris (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da matsayi na annabta da kuma ɗaukaka ambatonsa cikin talikai.

3. Babu wani nassi da ya inganta a kan cewa shi ma Annabi Idrisa yana nan raye, an ɗauke shi sama kamar yadda aka yi wa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Suratu Maryam (56-57)

وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ إِدۡرِيسَۚ إِنَّهُۥ كَانَ صِدِّيقٗا نَّبِيّٗا ٥٦ وَرَفَعۡنَٰهُ مَكَانًا عَلِيّٗا ٥٧

56. Kuma ka ambaci (labarin) Idrisu a cikin (wannan) Littafi (Alƙur'ani). Lalle shi ya kasance mai yawan gaskiya ne, Annabi.

57. Muka kuma ɗaukaka shi daraja maɗaukakiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ba da labarin Annabi Idris a cikin Alƙur'ani wanda shi ma Annabi ne da Allah ya ba shi yawan gaskiya da aiki da ita. Ya kuma ɗaukaka shi ya ba shi matsayi na annabta ya haɗa masa da *'Siddiƙiyya'*, wanda shi ma matsayi ne da ya ƙunshi cikakkiyar gaskatawa da cikakken ilimi da tabbataccen yaƙini tare da aiki na gari.
Ya zo a cikin hadisin Isra'in Annabi (ﷺ) cewa, ya haɗu da shi a sama ta huɗu. [Dubi, Bukhari #3207 da Muslim #162].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hanyar annabawa ita ce hanyar mutanen da Allah ya yi wa ni'ima, kuma ita ce hanyar da muke roƙon Allah a cikin sallolinmu da ya shiryar da mu zuwa gare ta.

2. Falalar sujjadar tilawa ga mai karatun Alƙur'ani da mai saurarensa.

3. Wannan ayar tana daga cikin wuraren sujjada a Alƙur'ani da aka ruwaito daga Annabi (ﷺ) domin koyi da waɗannan annabawa.

Suratu Maryam (58)

أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِن ذُرِّيَّةِ ءَادَمَ وَمِمَّنۡ حَمَلۡنَا مَعَ نُوحٖ وَمِن ذُرِّيَّةِ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡرَٰٓءِيلَ وَمِمَّنۡ هَدَيۡنَا وَٱجۡتَبَيۡنَآۚ إِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُ ٱلرَّحۡمَٰنِ خَرُّواْ سُجَّدٗا وَبُكِيّٗا ٥٨

58. Waɗannan su ne annabawa waɗanda Allah Ya yi ni'ima a gare su, daga zuriyar Adamu, da kuma waɗanda Muka ɗauko (a jirgin ruwa) tare da Nuhu, daga kuma zuriyar Ibrahimu da Isra'ila (watau Ya'aƙubu), da kuma waɗanda Muka shiryar da su Muka kuma zaɓe su. Idan ana karanta musu ayoyin (Allah) Mai rahama sai su faɗi su yi sujjada suna kuka.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci jinsin annabawa gaba ɗaya bayan ya gabatar da ambaton ɗaiɗaikunsu, da cewa waɗannan annabawa su ne mutanen da Allah ya yi wa ni'ima wadda babu irinta, ya ba su annabta da manzanci ya kuma umarce su da su kira mutane zuwa ga tafarki madaidaici.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci cewa sashin waɗannan annabawa sun fito ne daga zurriyyar Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), wasu kuma sun fito daga zurriyyar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), a yayin da wasunsu kuma sun fito ne daga zurriyar Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da jikansa Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Waɗannan gidaje su ne mafi darajar gidaje a duniya, Allah ya zaɓe su ya fifita su.

Allah kuma ya bayyana wani kyakkyawan halinsu na tsoron Allah da girmama maganarsa, da cewa, idan an karanta musu ayoyin Allah mai rahama suka ji abubuwan da suka ƙunsa na siffofin Allah da batun ranar lahira da sakamakon wuta ko Aljanna, sai su faɗi su yi sujjada suna kuka.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haɗarin wasa da salla, kuma mai yin haka zai gamu da azaba mai tsanani ranar alƙiyama idan bai tuba ba.

2. Duk wanda ya tuba to ana kankare masa munanan ayyukansa da suka gabata, kuma ba za a tauye masa ladan ayyukansa masu kyau ba. Wannan yana tabbatar da cikakken karamci na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Aljanna a lahira gidaje ne masu yawa ba guda ɗaya ce ba, sannan kuma matakai ne daban-daban kowa daidai gwargwadon aikinsa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jingina Aljanna zuwa ga sunansa 'Mai rahama' domin tana ƙunshe da rahama da kyautatawa wadda ido bai taɓa gani ba, kunne kuma bai taɓa ji ba, sannan ba ta taɓa ɗarsuwa a zuciyar wani mutum ba.

5. Bayin Allah mai rahama, ana nufin bayinsa waɗanda suka bauta masa shi kaɗai tare da rungumar shari'o'insa da neman yardarsa.

Suratu Maryam (59-63)

۞فَخَلَفَ مِنۢ بَعۡدِهِمۡ خَلۡفٌ أَضَاعُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَٱتَّبَعُواْ ٱلشَّهَوَٰتِۖ فَسَوۡفَ يَلۡقَوۡنَ غَيّٗا ٥٩ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَأُوْلَٰٓئِكَ يَدۡخُلُونَ ٱلۡجَنَّةَ وَلَا يُظۡلَمُونَ شَيۡـٔٗا ٦٠ جَنَّٰتِ عَدۡنٍ ٱلَّتِي وَعَدَ ٱلرَّحۡمَٰنُ عِبَادَهُۥ بِٱلۡغَيۡبِۚ إِنَّهُۥ كَانَ وَعۡدُهُۥ مَأۡتِيّٗا ٦١ لَّا يَسۡمَعُونَ فِيهَا لَغۡوًا إِلَّا سَلَٰمٗاۖ وَلَهُمۡ رِزۡقُهُمۡ فِيهَا بُكۡرَةٗ وَعَشِيّٗا ٦٢ تِلۡكَ ٱلۡجَنَّةُ ٱلَّتِي نُورِثُ مِنۡ عِبَادِنَا مَن كَانَ تَقِيّٗا ٦٣

59. Sai wasu suka maye gurbinsu bayansu waɗanda suka tozarta salla suka kuma bi sha'awace-sha'awacen (duniya na saɓo); to ba da daɗewa ba za su haɗu da mummunan sharri (a Jahannama).

60. Sai dai wanda ya tuba ya yi imani ya kuma yi aiki na gari, to waɗannan za su shiga Aljanna, kuma ba za a tauye musu komai ba.

61. (Watau) gidajen Aljanna na dindindin waɗanda (Allah) Mai rahama Ya yi wa bayinsa alƙawari da su alhali ba su gan su ba. Lalle alƙawarinsa kuwa ya tabbata mai zuwa ne.

62. Ba za su ji wani zancen banza ba a cikinsu sai sallama (daga mala'iku); kuma arzikinsu na nan tare da su a cikinsu safe da yamma.

63. Waccan ita ce Aljannar da za Mu gadar da ita ga wanda ya zamo mai taƙawa daga cikin bayinmu.

A waɗannan ayoyi bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin annabawa masu biyayya ga umarninsa da girmama shi da jin tsoronsa, sai kuma ya kawo bayanin wasu bara-gurbin mutane waɗanda suka maye gurbin waɗanda suka gabace su. Ya bayyana cewa, su waɗannan sun tozarta salla wadda ita ce mafi girman rukunin addinin Musulunci bayan Kalmar Shahada, ba su kiyaye ta ba da yin ta a kan lokacinta tare da

sharuɗɗanta, suka bi sha'awace-sha'awacensu na saɓon Allah da tozarta umarninsa. Don haka Allah ya tabbatar musu da cewa, za su gamu da matsananciyar azaba a wutar Jahannama.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Abin da yake tsakanin bawa da shirka shi ne barin salla." [Muslim #82].

An karɓo daga Buraida ɗan Husaibu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Alƙawarin da ke tsakaninmu da su (watau kafirai) ita ce salla, don haka wanda ya bar ta ya kafirta." [Tirmizi #2621 da Nasa'i #463].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya togace waɗanda suka tuba suka dawo suka kula da sallolinsu kamar yadda ya kamata suka watsar da bin sha'awace-sha'awacensu na duniya suka yi nadama a kan abin da suka aikata da niyyar ba za su ƙara ba nan gaba, suka kuma yi imani da Allah da ranar lahira tare da yin ayyuka na gari waɗanda shari'a ta umarce su da aikatawa. To waɗanan Allah ya yi musu alƙawarin shigar da su gidan Aljanna kuma ba za a tauye musu komai na ladan ayyukansu da suka yi ba, kuma ba za a zarge su da laifukan da ba su aikata ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffofin gidajen Aljanna da zai saka masu bin umarninsa, da cewa su gidajen Aljanna ne waɗanda za a dawwama a cikinsu har abada ba za su gushe ba. Su ne waɗanda Allah mai rahama ya yi wa bayinsa na gari alƙawarin su ba tare da sun gan su ba, amma kuma sun ba da gaskiya da su, sun kuma yi ta yin aiki tuƙuru domin su same su. Allah ya tabbatar musu da cewa alƙawarinsa mai zuwa ne domin ba ya saɓa alƙawari.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) a cikin wani dogon hadisi ya ce: "Allah zai tambayi mala'iku game da bayinsa masu zama suna ambatonsa cewa: "Me suke nema?" Sai su ce: "Suna neman Aljanna ne." Sai ya ce: "Shin sun taɓa ganin ta?" Sai su ce: "A'a." Sai ya ce: "To ƙaƙa da a ce sun taɓa ganin ta?" Sai mala'iku su ce: "Ai da sun taɓa ganin ta da sai sun fi haka tsananin kwaɗayin ta da neman ta." [Bukhari #6408 da Muslim #7424].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ambaton siffofin Aljanna da cewa 'yan Aljanna ba za su taɓa jin wata maganar banza ba a cikin gidan aljannar sai dai maganar aminci, kamar sallamar mala'iku gare su da ambaton Allah da hirar farin ciki da nishaɗi. Hakanan za a riƙa kawo musu kayayyakin ciye-ciye da shaye-shaye da safe da yamma irin wanda suka nuna suna buƙata.
Sai kuma ya bayyana cewa, wannan shi ne gidan Aljanna da yake gadar da shi ga bayinsa masu kiyaye dokokinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mala'iku ba sa saukowa ƙasa sai da umarnin Allah, domin ba sa yin komai da gaban kansu sai an ba su izini.

2. Annabi (ﷺ) koyaushe yana kwaɗayin ganin Mala'ika Jibrilu ya zo masa, domin yana samun ɗebewar kewa da sauraron wahayi da yake zuwa masa da shi.

3. Ubangiji mai cikakken sani ne, don haka mantuwa ba ta samun iliminsa ko kaɗan.

4. Bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) na buƙatar haƙuri da juriya saboda yaƙin da Shaiɗan yake yi da zuciyar bawa don ya shagaltar da shi daga Ubangijinsa.

5. Babu wani mahaluƙi da ya yi kama da Allah ta kowane ɓangare ballantana har ya cancanci a bauta masa tare da Allah ko a jingina masa wani aikin da Allah ya keɓanta da shi.

Suratu Maryam (64-65)

وَمَا نَتَنَزَّلُ إِلَّا بِأَمۡرِ رَبِّكَۖ لَهُۥ مَا بَيۡنَ أَيۡدِينَا وَمَا خَلۡفَنَا وَمَا بَيۡنَ ذَٰلِكَۚ وَمَا كَانَ رَبُّكَ نَسِيّٗا ٦٤ رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا فَٱعۡبُدۡهُ وَٱصۡطَبِرۡ لِعِبَٰدَتِهِۦۚ هَلۡ تَعۡلَمُ لَهُۥ سَمِيّٗا ٦٥

64. (Mala'ika Jibrilu ya ce): "Ba ma sauka sai da umarnin Ubangijinka; abin da yake gabanmu da wanda yake bayanmu da kuma abin da yake tsakanin waɗannan (duka) nasa ne. Ubangijinka kuma bai zama Mai mantuwa ba.

65. "(Shi ne) Ubangijin sammai da ƙasa da kuma abin da yake tsakaninsu, sai ka bauta masa kuma ka yi haƙuri ga bautarsa. Shin ka san wani tamkarsa?"

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne ya umarci Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya ba wa Annabi (ﷺ) amsar tambayar da ya yi masa game da rashin zuwansa na wani ɗan lokaci.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi): "Me yake hana ka ziyartar mu kamar yadda ka saba ziyartar mu?" Sai wannan ayar ta 64 ta sauka. [Bukhari #4731].

A cikin ayar, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mala'ika Jibrilu da ya faɗa wa Manzon Allah (ﷺ) cewa: Su mala'iku ba sa saukowa ƙasa sai da izinin Allah, domin babu abin da suke aikatawa sai da umarninsa. Ya kuma bayyana masa cewa abin da suke tunkara a nan gaba na al'amarin lahira, da wanda suke ba shi baya na duniya, da abin da yake tsakanin duniya da lahira duk na Allah ne, mulkinsa ne sai yadda ya ga dama zai kasance. Ya kuma ƙara tabbatar masa da cewa, Ubangijinsa Allah bai zama mai manta wani abu ba, don haka ba zai manta da shi ba, bai gushe ba yana jiɓintar al'amarinsa yana tsara masa komai yadda ya dace.
Sai kuma ya bayyana Rububiyyar Allah ga sammai da ƙasa, watau shi ne wanda ya samar da su daga babu, kuma yake tafiyar da su yadda ya ga dama, don haka kada Manzon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shagaltar da kansa game da wannan, shi dai ya ci gaba da haƙuri da juriya wajen bautar Allah da watsi da ƙyale-ƙyalen duniya. Sannan ya tabbatar da cewa shi Allah ba ya da mai kama da shi a sunayensa da siffofinsa da ayyukansa, shi kaɗai ne kammalalle ta kowace fuska, don haka shi ne kaɗai ya cancanci a bauta masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira zuwa ga amfani da nazari na hankali don tabbatar da aƙidar tashi bayan mutuwa. Hakan ya nuna cewa ƙaryata tashi bayan mutuwa tsantsar rafkanuwa ce da rashin tuna halittar farko.

2. Za a tashi kowane ɓatacce daga ƙabarinsa tare da shedaninsa domin gurfanar da su gaban Allah don ya yi musu hisabi.

3. Tabbatar da cikakken adalcin Allah, domin zai yi wa duk masu laifi sakamako ne kowa gwargwadon laifinsa.

Suratu Maryam (66-70)

وَيَقُولُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَءِذَا مَا مِتُّ لَسَوۡفَ أُخۡرَجُ حَيّٗا ٦٦ أَوَ لَا يَذۡكُرُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَنَّا خَلَقۡنَٰهُ مِن قَبۡلُ وَلَمۡ يَكُ شَيۡـٔٗا ٦٧ فَوَرَبِّكَ لَنَحۡشُرَنَّهُمۡ وَٱلشَّيَٰطِينَ
ثُمَّ لَنُحۡضِرَنَّهُمۡ حَوۡلَ جَهَنَّمَ جِثِيّٗا ٦٨ ثُمَّ لَنَنزِعَنَّ مِن كُلِّ شِيعَةٍ أَيُّهُمۡ أَشَدُّ عَلَى ٱلرَّحۡمَٰنِ عِتِيّٗا ٦٩ ثُمَّ لَنَحۡنُ أَعۡلَمُ بِٱلَّذِينَ هُمۡ أَوۡلَىٰ بِهَا صِلِيّٗا ٧٠

66. Kuma mutum (watau kafiri) yana cewa: “Yanzu idan na mutu anya kuwa za a ta da ni da rai?”

67. Yanzu shi kafiri ba zai tuna ba cewa Mu Muka halicce shi tun farko kafin ya zama komai?

68. To na rantse da Ubangijinka lalle za Mu tashe su tare da shaiɗanu, sannan za Mu kawo su a gaban Jahannama suna a duddurƙushe.

69. Sannan daga kowace jamaꞌa lalle za Mu ware waɗanda suka fi tsananin yi wa (Allah) Mai rahama tsaurin kai.

70. Sannan babu shakka Mu Muka fi sanin waɗanda suka fi cancanta da ƙonuwa da ita (watau wuta)

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda mutum kafiri yake ƙaryata tashin mutane da ransu bayan sun mutu domin a yi musu hisabi ranar alƙiyama, yana ganin ta yaya za a iya sake tashin sa da rai bayan ya zama ragargazajjen ƙashi? To sai Allah ya faɗa masa wani dalili mai ƙarfi da kowane mai hankali zai fahimta mai kuma nuna yiwuwar abin da yake ƙaryatawa. Allah ya faɗa masa cewa, yanzu ba zai waiwayi bayansa ba ya tuna cewa Allah ne ya halicce shi bayan a da babu shi; to me zai hana ya iya sake halittar sa a karo na biyu domin yi masa hisabi? Babu shakka wanda ya halicce shi lokacin da babu shi, tabbas yana da ikon sake dawo da halittarsa bayan ya zama ƙasusuwa ratattakakku.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: Allah ya ce: “Ɗan’adam ya ƙaryata ni, bai kuma dace ya ƙaryata ni ba, ya kuma zage ni, bai dace kuma ya zage ni ba. Amma ƙaryata ni da ya yi shi ne ya riya cewa ba zan iya dawo da shi ba kamar yadda yake. Zagi na kuwa da ya yi shi ne faɗar cewa ina da mata da ɗa.” [Bukhari #4482].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da Rububiyyarsa ga masu ƙaryata tashi bayan mutuwa domin yin hisabi, da cewa lalle zai tashe su tare da shaiɗanunsu ya tara su domin yi musu hisabi, ya kuma tabbatar musu cewa lalle zai kawo su gaban Jahannama a duddurƙushe a kan gwiwoyinsu suna cike da tsoro da fargabar azabar da take jiran su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin da zai yi musu a wannan ranar da cewa, lalle zai fito da shugabannin kafirci da zalunci daga kowace ƙungiya ta masu addinin ƙarya da ƙungiyoyin azzalumai domin su jagoranci mabiyansu zuwa azabar da take jiran su. Don haka za a sa su a layi gwargwadon girman kafircin kowa da zaluncinsa.

Sai kuma ya bayyana cewa duk zai yi haka ne saboda cikar adalcinsa da yalwar iliminsa, ya tabbatar da cewa ya fi kowa sanin wanda ya fi cancantar shiga wuta, domin ya san ayyukan kowa da gwargwadon irin azabar da ta dace da laifinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da ƙetare Siraɗi a lahira ga dukkan mutane, kowa gwargwadon aikinsa.

2. Babu abin da zai amfani bawa a ranar alƙiyama yayin tsallake Siraḍî sai taƙawarsa.

3. Haḍarin zalunci da illarsa a ranar alƙiyama.

4. Babu wata alaƙa tsakanin jin daḍin wani mutum a duniya da kuma karɓuwarsa a wurin Allah. Samun jin daḍî da ƙyale-ƙyale na duniya ba ya nuna cewa Allah ya yarda da wannan bawan nasa ko abin da yake kai gaskiya ne. Hakanan rashin samun wadatar duniya da jin daḍinta ba ya nuna rashin karɓuwar wannan bawa a wurin Allah ko kuma abin da yake kai ba gaskiya ne ba.

Suratu Maryam (71-74)

وَإِن مِّنكُمْ إِلَّا وَارِدُهَا ۚ كَانَ عَلَىٰ رَبِّكَ حَتْمًا مَّقْضِيًّا ﴿٧١﴾ ثُمَّ نُنَجِّي ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّنَذَرُ ٱلظَّٰلِمِينَ فِيهَا جِثِيًّا ﴿٧٢﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ قَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَىُّ ٱلْفَرِيقَيْنِ خَيْرٌ مَّقَامًا وَأَحْسَنُ نَدِيًّا ﴿٧٣﴾ وَكَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّن قَرْنٍ هُمْ أَحْسَنُ أَثَٰثًا وَرِءْيًا ﴿٧٤﴾

71. Ba kuma ḍaya daga cikinku face sai ya bi ta kanta (watau wutar Jahannama). (Wannan) ya kasance tabbataccen abu abin hukuntawa a wurin Ubangijinka.

72. Sannan kuma za Mu tserar da waḍanda suka kiyaye dokokin Allah Mu kuma bar kafirai a duddurƙushe cikinta.

73. Kuma idan ana karanta musu ayoyinmu bayyanannu sai waḍanda suka kafirta su ce da waḍanda suka yi imani: “Wane ne daga cikin ƙungiyoyin nan biyu (watau muminai da kafirai) yake da mafificin matsayi da kuma mafi kyan majalisa?”

74. Kuma al’umma nawa Muka hallaka a gabanninsu waḍanda suke da mafi kyan abin duniya da kyawun gani.

A waḍannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ḍaukaka) yana magana ne da dukkan halittunsa, muminai da kafirai, na kirki da na banza, na farko da na ƙarshe, yana tabbatar musu da cewa, kowa daga cikinsu sai ya bi ta kan Jahannama, watau ta kan Siraḍî da zai shimfiḍa shi a kan doron wutar Jahannama a nemi kowa ya tsallaka ta kansa. Allah ya bayyana cewa wucewa ta kansa tabbataccen abu ne da ya riga ya hukunta sai ya faru. Mutane za su wuce ta kan Siraḍî kowa gwargwadon aikinsa, wasu za su wuce kamar ƙiftawar ido, wasu kuma kamar gudun iska, wasu kuma kamar sukuwar dawakai, akwai kuma masu gudu da ƙafafu, akwai kuma masu tafiya, akwai kuma masu jan ciki, sannan da akwai waḍanda za a finciko su a jefa su wutar Jahannama; kowa dai gwargwadon tsoronsa ga Allah (Mai tsarki da ḍaukaka). wanda ya zo a cikin hadisai masu yawa.

Sai Allah (Mai tsarki da ḍaukaka) ya bayyana cewa zai tserar da masu taƙawa, waḍanda suka kiyaye dokokin Allah, suka aikata abubuwan da ya umarce su da shi, suka kuma bar waḍanda ya hana su. Sai kuma ya ƙyale azzalumai waḍanda suka cuci kawunansu da kafirci da saɓon Allah, a cikin wutar Jahannama a guggurfane a kan gwiwoyinsu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ḍaukaka) ya bayyana halin kafirai idan suna jin ana karanta ayoyin Allah bayyanannu masu nuna kaḍaitakar Allah da gaskiyar manzanninsa, sai su ce wa muminai: Mu da ku wane ne ya fi matsayi a duniya na yawan dukiya da yawan ‘ya’ya? Kuma wane ne ya fi kyan majalisa?! Watau suna nuna cewa, da a kan gaskiya suke, su kuma suna kan ƙarya, to da muminai sun fi su jin daḍin duniya, wai saboda Allah mai hikima ne ba zai bar masoyansa cikin wahala da ƙasƙanci ba, ya kuma ba wa maƙiyansa rayuwar jin daḍî da ḍaukaka.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani gamsasshe inda ya tabbatar musu cewa ya hallaka al'ummu da yawa kafin waɗannan kafiran masu alfahari da yawan dukiya da tarin ‘ya’ya da ƙyale-ƙyale na duniya, waɗanda sun fi su tarin dukiya da kyau na gani a faɗa saboda tsadar tufafin da suke sanyawa da hutun da ke tattare da su ya fi na waɗannan kafiran nesa ba kusa ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda ya nutse cikin ɓata ya rungumi kafirci, to Allah zai yi watsi da shi ya ci gaba da rayuwa cikin jahilcinsa da kafircinsa, don ya jima yana ruɗar kansa, daga ƙarshe ya haɗu da mummunar azaba a ranar lahira.

2. Imanin mumini yana ƙaruwa ne ta hanyar ɗa’a ga Allah da Manzonsa.

3. Shiriya ta ƙunshi ilimi mai amfani da aiki na gari; wanda duk ya kama hanyar neman ilimi ya rungumi ayyuka na ƙwarai, to Allah zai hore masa hanyar samun biyan buƙatarsa, ya yi masa tukwici da wasu abubuwa waɗanda aikinsa da ƙwazonsa ba zai ba shi su ba.

4. Wanzazzun ayyuka kyawawa sun ƙunshi duk wani aikin ɗa’a ga Allah, kamar salla da zakka da azumi da hajji da umara da karatun Alƙur’ani da zikiri da kyautata wa mutane, duk waɗannan ayyuka ne da ladansu dawwamamme ne.

Suratu Maryam (75-76)
قُلۡ مَن كَانَ فِي ٱلضَّلَٰلَةِ فَلۡيَمۡدُدۡ لَهُ ٱلرَّحۡمَٰنُ مَدًّاۚ حَتَّىٰٓ إِذَا رَأَوۡاْ مَا يُوعَدُونَ إِمَّا ٱلۡعَذَابَ وَإِمَّا ٱلسَّاعَةَ فَسَيَعۡلَمُونَ مَنۡ هُوَ شَرّٞ مَّكَانٗا وَأَضۡعَفُ جُندٗا ٧٥ وَيَزِيدُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ٱهۡتَدَوۡاْ هُدٗىۗ وَٱلۡبَٰقِيَٰتُ ٱلصَّٰلِحَٰتُ خَيۡرٌ عِندَ رَبِّكَ ثَوَابٗا وَخَيۡرٞ مَّرَدّٗا ٧٦

75. Ka ce (da su): “Wanda ya zamana yana cikin ɓata to (Allah) Mai rahama zai tsawaita ransa Ya yalwata masa; Har sai sanda suka ga abin da ake yi musu alƙawari da shi ne, ko dai azaba (a duniya) ko kuma tashin alƙiyama, to fa za su san wane ne ya fi mummunan matsayi da kuma (wanda) ya fi raunin mataimaka.”

76. Kuma Allah Yana ƙara shiryar da waɗanda suka bi hanyar shiriya. Wanzazzun ayyuka na gari kuma su suka fi lada a wurin Ubangijinka, suka kuma fi kyakkyawan ƙarshe.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya bayyana wa kafirai masu alfahari da yawan abin duniya da ƙyale-ƙyalenta cewa, duk wani wanda ya zaɓi ɓata a kan shiriya, to Allah zai ƙara masa ɓata a kan ɓatansa; ya ƙara masa son ɓata don ya zamanto uƙuba gare shi, har sai su masu irin waccan magana sun ga abin da ake yi musu alƙawarinsa, ko dai azaba a nan duniya ta hanyar kisa da kamu ko kuma tashin alƙiyama ranar da za su ga sakamakon ayyukansu, to a nan za su tantance su wane ne tsakanin su da muminai suka fi mummunan matsayi, suka fi kuma raunin mataimaka?
Sai kuma ya bayyana cewa, muminai waɗanda suka zaɓi shiriya yana ƙara musu shiriya daga falalarsa da rahamarsa, kuma ayyuka na ƙwarai masu wanzuwa da tabbata sun fi amfani a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta wajen samun kyakkyawan sakamako da kuma kyakkyawar makoma.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sakarcin kafiri da tunaninsa na shirme da burace-buracensa marasa tushe.

2. Wajibi ne mutum ya kiyayi abin da harshensa zai riƙa furtawa, domin ana rubuta komai kuma za a bijiro masa da shi ranar alƙiyama.

3. Kowa zai koma ne ga Allah shi kaɗai ya bar duk abin da ya mallaka a nan duniya na dukiya da ‘ya‘ya da dangi.

Suratu Maryam (77-80)
أَفَرَءَيْتَ ٱلَّذِى كَفَرَ بِـَٔايَـٰتِنَا وَقَالَ لَأُوتَيَنَّ مَالًا وَوَلَدًا ﴿٧٧﴾ أَطَّلَعَ ٱلْغَيْبَ أَمِ ٱتَّخَذَ عِندَ ٱلرَّحْمَـٰنِ عَهْدًا ﴿٧٨﴾ كَلَّا ۚ سَنَكْتُبُ مَا يَقُولُ وَنَمُدُّ لَهُۥ مِنَ ٱلْعَذَابِ مَدًّا ﴿٧٩﴾ وَنَرِثُهُۥ مَا يَقُولُ وَيَأْتِينَا فَرْدًا ﴿٨٠﴾

77. Shin kuwa ka ga wanda ya kafirce wa ayoyinmu, ya kuma ce: “Lalle tabbas za a ba ni dukiya da ‘ya’yaye?”

78. Shin ko ya san gaibu ne, ko kuwa ya sami alƙawari ne a wurin (Allah) Mai rahama?

79. A’a, ba haka ba ne. Za Mu rubuta abin da yake faɗa, za Mu kuma ƙara masa azaba ninkin-ba-ninkin.

80. Kuma Mu gaje abin da yake faɗa ɗin (na dukiyarsa da ‘ya’yansa), ya kuma zo mana shi kaɗai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin wani kafiri ne wanda baya ga kafircinsa har ma yana yi wa muminai izgili, yana furta cewa, shi fa ko a lahira sai Allah ya ba shi kuɗi da ‘ya’ya.

An karɓo daga Khabbab ɗan Arat (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Na kasance maƙeri, sai kuma ina bin Al-Asi ɗan Wa’ilu bashi, sai na je wajensa domin ya biya ni bashina, sai ya ce min: “Wallahi ba zan biya ka ba har sai ka kafirce wa Muhammad.” Sai na ce masa: “Wallahi ba zan kafirce wa Muhammad ba (ﷺ) har ka mutu a tashe ka.” Sai ya ce: “To je ka, idan na mutu aka tashe ni sai ka dawo in biya ka, domin ni idan an je can ma ni mai kuɗi ne da ‘ya’ya.” Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar ta 77-80.” [Bukhari #2091 da Muslim #2795].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Manzonsa cewa, shin ko ya ga mutumin da ya kafirce wa ayoyinsa da hujjojin da ya zo da su, amma kuma yana da’awar shi idan ya mutu an tashe shi to lalle sai an ba shi dukiya da ‘ya’ya? Watau yana nufin shi ɗan Aljanna ne; wannan abu da ban mamaki yake. To sai Allah ya bayyana ƙaryarsa, ya tambaye shi cewa, shin ya san gaibu ne da har ya gano shi ɗan Aljanna ne a lahira, ko kuma sun yi wani alƙawari ne da Allah na cewa zai ba shi dukiya da ‘ya’ya a lahira? Allah ya tabbatar da cewa, babu ko ɗaya daga waɗannan abubuwan, watau dai ƙaryarsa ce kawai yake sharawa. To sai Allah ya yi masa alƙawarin narko mai tsanani da cewa, zai rubuta duk waɗannan ƙazaman maganganu da yake furtawa domin yi masa hisabi a kansu, kuma ya ƙara masa azaba a Jahannama ninkin-ba-ninkin saboda hauhawar kafircinsa a nan duniya.
Sannan Allah ya bayyana cewa zai ɗauke shi kacokam ya raba shi da dukiyar da ‘ya’yan da yake taƙama da su, ya koma gare shi shi kaɗai tinƙinsa babu ko sutura a jikinsa, a inda zai ga mummunar azabar da take jiran sa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya riƙi wanin Allah ya dogara gare shi to zai tozarta shi a sanda ba ya zato.

2. Yayin da kafirai suka saki Allah suka ƙi yin riƙo da igiyarsa, suka haɗa shi da wasu wajen bauta suka kama maƙiyansa daga cikin shaiɗanu, sai Allah ya ɗora shaiɗanun a kansu suna ingiza su cikin kafirci da saɓon Allah tare da saka musu waswasi da ƙawata musu ƙarya da munana gaskiya a idanuwansu, don haka suke yaƙar ta suke yaƙar masu son gaskiya. Wannan duk sakamako ne na sakin Ubangiji da kama waninsa.

3. Babu mai haƙƙin yin ceto sai Allah shi kaɗai, kuma yana yin izinin ceto ne ga wanda ya yi imani da shi ya yi aiki na ƙwarai.

Suratu Maryam (81-87)

وَٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ ءَالِهَةً لِّيَكُونُواْ لَهُمۡ عِزّٗا ٨١ كَلَّاۚ سَيَكۡفُرُونَ بِعِبَادَتِهِمۡ وَيَكُونُونَ عَلَيۡهِمۡ ضِدّٗا ٨٢ أَلَمۡ تَرَ أَنَّآ أَرۡسَلۡنَا ٱلشَّيَٰطِينَ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ تَؤُزُّهُمۡ أَزّٗا ٨٣ فَلَا تَعۡجَلۡ عَلَيۡهِمۡۖ إِنَّمَا نَعُدُّ لَهُمۡ عَدّٗا ٨٤ يَوۡمَ نَحۡشُرُ ٱلۡمُتَّقِينَ إِلَى ٱلرَّحۡمَٰنِ وَفۡدٗا ٨٥ وَنَسُوقُ ٱلۡمُجۡرِمِينَ إِلَىٰ جَهَنَّمَ وِرۡدٗا ٨٦ لَّا يَمۡلِكُونَ ٱلشَّفَٰعَةَ إِلَّا مَنِ ٱتَّخَذَ عِندَ ٱلرَّحۡمَٰنِ عَهۡدٗا ٨٧

81. (Kafirai) kuma suka riƙi wasu abubuwan bauta ba Allah ba don su zama mataimaka a gare su.

82. A'a, ba haka ba ne. Ba da daɗewa ba za su kafirce wa bautar da suke yi musu, su kuma zama abokan gaba a gare su.

83. Shin ba ka san Mu Muka ɗora shaiɗanu a kan kafirai ba suna ingiza su (cikin ɓata) ingizawa?

84. To kada ka yi gaggawa a kansu; kawai dai Muna ƙididdige musu (kwanakinsu) ɗai da ɗai.

85. Ranar da za Mu tayar da masu taƙawa zuwa ga (Allah) Mai rahama a matsayin manyan baƙi.

86. Mu kuma kora kafirai zuwa Jahannama cikin tsananin ƙishirwa.

87. Ba wani mai ikon yin ceto sai wanda yake da alƙawari a wurin (Allah) Mai rahama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai waɗanda suka saki Allah suka kafirce wa manzanninsa sun riƙi wasu abubuwan bauta ba Allah ba don su zame musu mataimaka. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa ba za su sami wata biyan buƙata a wajensu ba, kuma babu wani taimako da za su yi musu, hasali ma za su kafirce wa bautar da suke yi musu ranar alƙiyama, su yi baram-baram da juna suna la'antar juna, su zama abokan gabar juna.
Sai kuma ya bayyana cewa ya ɗora shaiɗanu a kan kafirai suna ingiza su cikin ayyukan kafirci da saɓon Allah da katange hanyarsa.
Sai Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da kada ya nemi gaggauto da hallakarsu, domin Allah yana ƙididdige kwanakin rayuwarsu, idan kwanakinsu suka ƙare ajalinsu ya yi to azabar Allah za ta riske su duk inda suke. Sai kuma ya umarce shi da ya tuna ranar alƙiyama sanda Allah zai tattara muminai masu kiyaye dokokinsa, waɗanda suka aikata abin da ya umarce su suka bar abin da ya hana su, a matsayin manyan baƙi masu daraja ya karrama su. Su kuma kafirai ya kora su zuwa Jahannama suna cikin matsananciyar ƙishirwa, suna neman masu taimaka musu sun rasa, domin a ranar a cikinsu babu wani mai ikon yin ceto, domin ceto duka na Allah ne shi kaɗai, sai ga wanda ya sami izini daga Allah mai rahama saboda ya riƙe alƙawarin da ya yi na imani da Allah da manzanninsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin munin jingina wa Allah ɗa.

2. Halittu manya-manya kamar sammai da ƙassai da duwatsu da bishiyoyi da makamantansu duka Allah ya halicce su a kan aƙidar Tauhidi, watau kaɗaita Allah cikin komai da fahimtar munin shirka ko jingina wata tawaya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Duk wata halitta da Allah ya yi manya da ƙanana bayi ne na Allah.

4. Ilimin Allah ya game komai babu abin da yake ɓace masa (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Wajibi ne mutum ya sanya tsoron Allah kawai a zuciyarsa; kada ya zaɓi daɗaɗa wa wani komai kusancinsa da shi ya saɓa wa mahaliccinsa, domin kowa shi kaɗai tilo zai je wa Allah.

Suratu Maryam (88-95)
وَقَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱلرَّحۡمَٰنُ وَلَدٗا ٨٨ لَّقَدۡ جِئۡتُمۡ شَيۡـًٔا إِدّٗا ٨٩ تَكَادُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرۡنَ مِنۡهُ وَتَنشَقُّ ٱلۡأَرۡضُ وَتَخِرُّ ٱلۡجِبَالُ هَدّٗا ٩٠ أَن دَعَوۡاْ لِلرَّحۡمَٰنِ وَلَدٗا ٩١ وَمَا يَنۢبَغِي لِلرَّحۡمَٰنِ أَن يَتَّخِذَ وَلَدًا ٩٢ إِن كُلُّ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ إِلَّآ ءَاتِي ٱلرَّحۡمَٰنِ عَبۡدٗا ٩٣ لَّقَدۡ أَحۡصَىٰهُمۡ وَعَدَّهُمۡ عَدّٗا ٩٤ وَكُلُّهُمۡ ءَاتِيهِ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فَرۡدًا ٩٥

88. Suka kuma ce: “(Allah) Mai rahama (wai) yana da ɗa.

89. Haƙiƙa kun zo da babban abu (marar daɗin ji).

90. Sama ta kusa ta kece saboda shi (mummunan furucin), ƙasa kuma ta tsage, duwatsu kuma su zube su yi rugu-rugu.

91. Saboda sun yi da’awar Allah Yana da ɗa!

92 Bai kuwa dace da (Allah) Mai rahama Ya zama Yana da ɗa ba.

93. Ba wani abu da yake cikin sammai da ƙasa face ya zo wa (Allah) Mai rahama a matsayin bawa.

94. Lalle Ya kiyaye da su Ya kuma ƙididdige su sosai.

95. Kuma dukkansu kowa zai zo masa a ranar alƙiyama shi kaɗai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wasu Yahudu da Nasara da ma wasu mushirikai sun yi da’awar cewa yana da ɗa. Allah ya nuna cewa masu irin wannan mummunar magana sun zo da wani babban abu wanda girman muninsa ya kusa ya sanya sammai su kekkece ƙasa kuma ta tsattsage duwatsu kuma su zube ƙasa su yi rugu-rugu, saboda sun jingina wa Allah ɗa alhali bai dace ba ko kaɗan Allah mai rahama ya zamana yana da ɗa. Shi ɗa yana nuna buƙatuwa ne, Allah kuma mai cikakkiyar wadata ne ba ya da buƙata a wajen kowa, duk mala’ikun da suke sammai da halittun da suke ƙasa na mutane da aljannu da wasunsu za su je wa Allah mai rahama a matsayin bayi ranar alƙiyama suna masu ƙaskantar da kawunansu ga Allah mahaliccinsu, dukkansu suna ƙarƙashin ikonsa. Ya tabbatar da cewa, iliminsa ya

kewaye su baki ɗaya kuma a lissafe suke a wurinsa ɗaya bayan ɗaya. Kuma dukkansu kowa shi kaɗai zai je wa Allah ranar alƙiyama babu kowa babu komai tare da shi sai ayyukansa.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wanda ya kai Allah haƙurin sauraron mummunan furuci; suna cewa wai Allah yana da ɗa amma duk da haka yana ba su lafiya yana arzuta su." [Bukhari #6099 da Muslim #2804].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah yana son bayinsa muminai masu ayyuka na gari yana jefa ƙaunarsu a cikin zukatan waliyyansa na sama da ƙasa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sauƙaƙe lafuzzan Alƙur'ani da ma'anoninsa domin cimma babbar manufar saukar da shi, watau wa'azi da tunatarwa ga mutane ta hanyar albishir da gargaɗi.

3. Gargaɗi ga azzalumai kada abin da ya sami ire-irensu a baya su ma ya same su, sai Allah ya hallakar da su kamar yadda ya hallakar da waɗancan.

Suratu Maryam (96-98)
إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَيَجۡعَلُ لَهُمُ ٱلرَّحۡمَٰنُ وُدّٗا ٩٦ فَإِنَّمَا يَسَّرۡنَٰهُ بِلِسَانِكَ لِتُبَشِّرَ بِهِ ٱلۡمُتَّقِينَ وَتُنذِرَ بِهِۦ قَوۡمٗا لُّدّٗا ٩٧ وَكَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم مِّن قَرۡنٍ هَلۡ تُحِسُّ مِنۡهُم مِّنۡ أَحَدٍ أَوۡ تَسۡمَعُ لَهُمۡ رِكۡزًا ٩٨

96. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki na gari, to (Allah) Mai rahama zai sanya musu ƙauna.

97. To Mun dai sauƙaƙe shi (Alƙur'ani) da harshenka ne don kawai ka yi wa masu taƙawa albishir da shi, ka kuma gargaɗi mutane masu tsananin jayayya da shi.

98. Al'umma nawa Muka hallaka a gabaninsu, shin kana jin ɗuriyar wani daga cikinsu, ko kuwa kana jin 'yar muryarsu?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rufe wannan Sura ne da bayyana tanadin ni'imarsa da ya yi wa waɗanda suka yi imani suka yi aiki na ƙwarai, ya yi musu alƙawarin zai sa farin jininsu a zukatan muminai masoyansa a sama da ƙasa, dukkanin bayinsa na gari su so su su ƙaunace su a zukatansu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan Allah yana son bawa sai ya kirawo Jibrilu ya ce masa: "Allah yana son wane, don haka kai ma ka so shi." Sai Jibrilu shi ma ya yi shela a cikin mala'iku da ke sama ya ce: "Lalle Allah yana son wane don haka ku ma ku so shi". Sai mala'iku a sama dukkansu su so shi sannan sai a ba shi karɓuwa a bayan ƙasa." [Bukhari #3209 da Muslim #2637].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata babbar ni'imarsa ga bayinsa, watau yadda ya sauƙaƙe Alƙur'ani da harshen Manzonsa (ﷺ) don ya yi wa mutane wa'azi da shi, ya yi wa masu bin dokokin Allah sau-da-ƙafa albishir na samun babban rabo da gwaggwaɓan sakamako a wurin Allah, ya kuma gargaɗi mutanen da suka yi ƙaurin suna a kafirci da saɓon Allah da shi Alƙur'ani, ya kuma tsayar musu hujja bayyananniya.

Sannan Allah ya tsoratar da kafirai ta hanyar bayyana musu yadda ya hallaka al'ummu da yawa da suka gabace su saboda kafircinsu da ƙaryata manzanninsu, kamar mutanen Annabi Nuhu da Adawa da Samudawa da Fir'auna da mutanensa, waɗanda dukkansu a yanzu babu wanda ake iya jin ɗuriyarsa sai dai a labarai da karatun tarihi. To wannan kaɗai ya isa ya zama wa'azi a gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɗaha, waɗannan haruffa ne da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wasu surori da ire-irensu, kuma nuni ne zuwa ga mu'ujizar Alƙur'ani. Amma maganar cewa 'Ɗaha' ɗaya ne daga sunayen Manzon Allah ba ingantacciya ce ba.

2. A Shari'a babu wani abu da aka shar'anta shi don ya jigatar da mai yinsa. Shari'a rahama ce da tausayawa ga muminai, kuma hanya ce mai isar da bayi zuwa ga dacewa da kyakkyawar rayuwa ta duniya da lahira.

3. Alƙur'ani ya ƙunshi wa'azi da faɗakarwa ga mutane ta hanyar tsoratarwa don su guji abin da zai hallaka su ya jefa su cikin hasara a duniya da lahira; kuma kwaɗaitarwa ne ga ayyukan da za su samar musu da yardar Allah da hukunce-hukunce masu cike da hikimomi da adalci.

4. An keɓe 'mai tsoron Allah' da ambato wajen wa'azantuwa domin shi kaɗai ne mai amfana da shi; wanda bai yi imani da Aljanna da wuta ba babu kuma imani a zuciyarsa, ba zai taɓa amfana da Alƙur'ani ba.

5. Bayanin ɗaukakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da daidaitonsa a kan Al'arshi.

6. Wajibi ne bawa ya zama mai tsoron Allah da kiyaye dokokinsa a duk inda yake kuma a kowanne lokaci, domin Allah masanin komai ne na bayyane da na ɓoye.

7. Sunayen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sun kai matuƙa wajen kyau, domin suna ƙunshe da kyakkyawan yabo ga Allah, kuma masu nuna siffofin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) maɗaukaka masu cike da kamala.

8. Yana daga cikin kyawun sunayen Allah cewa ya yi umarni da a roƙe shi da su, domin yin haka yana kusantar da mai addu'a zuwa gare shi, kuma yana son sunayensa yana kuma son masu son su masu bincike a kan ma'anoninsu don su bauta masa da su.

20-Suratu Ɗa Ha

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da sunan '*Suratu Ɗaha'*, watau da haruffa guda biyu da aka buɗe ta da su.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Wannan Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba'in da biyar (45) a jerin saukar surorin Alƙur'ani; ta sauka bayan '*Suratu Maryam'* kafin '*Suratul Waƙi'a'*.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Makka da Madina ayoyinta ɗari ne da talatin da huɗu (134). A kuma lissafin mutanen Sham adadinsu ɗari da arba'in ne (140). Amma a wurin mutanen Kufa kuwa adadinsu ɗari da talatin da biyar ne (135).

5. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne lallashin Manzon Allah (ﷺ) game da ƙalubalen da yake fuskanta daga kafirai da nuna masa irin yadda wasu annabawan da suka gabace shi su ma suka fuskanci ƙalubale iri-iri, amma suka jure, daga ƙarshe Allah ya ba su nasara.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Kalubalantar Larabawa su kawo wani abu kamar Alƙur'ani in sun isa.
• Ishara zuwa ga cewa Alƙur'ani shiriya ne ga waɗanda za su karɓi shiriyar Allah su yi aiki da ita.
• Bayanin girman Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da tabbatar da manzancin Annabi (ﷺ) da bayanin cewa manzancinsa ya yi kama da manzancin wani babban annabi da aka aiko kuma labarinsa ya cika ko'ina da ina, watau Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Aka kuma kwatanta saukar da Alƙur'ani da maganar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
• Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi cikakken bayanin tasowar Annabi Musa da nasarar da Allah ya ba shi a kan Fir'auna da mutanensa.
• Labarin Assamiri da yadda ya sassaƙa ɗan maraƙi ya umarci Banu Isra'ila suka bauta masa bayan tafiyar Annabi Musa don ganawa da Ubangijinsa.
• Bayanin tsananin gabar Shaiɗan ga 'yan'adam.
• Lallashin Annabi (ﷺ) a kan maganganun da kafirai suke faɗa masa marasa daɗi.
• Da sauran batutuwa da suka danganci tashin alƙiyama da abubuwan da suke da alaƙa da hakan.

Suratu Ɗa Ha (1-8)

طه ﴿١﴾ مَآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡقُرۡءَانَ لِتَشۡقَىٰٓ ﴿٢﴾ إِلَّا تَذۡكِرَةٗ لِّمَن يَخۡشَىٰ ﴿٣﴾ تَنزِيلٗا مِّمَّنۡ خَلَقَ ٱلۡأَرۡضَ وَٱلسَّمَٰوَٰتِ ٱلۡعُلَى ﴿٤﴾ ٱلرَّحۡمَٰنُ عَلَى ٱلۡعَرۡشِ ٱسۡتَوَىٰ ﴿٥﴾ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا وَمَا تَحۡتَ ٱلثَّرَىٰ ﴿٦﴾ وَإِن تَجۡهَرۡ بِٱلۡقَوۡلِ فَإِنَّهُۥ يَعۡلَمُ ٱلسِّرَّ وَأَخۡفَى ﴿٧﴾ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ لَهُ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ ﴿٨﴾

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ƊaHa.

2. Ba Mu saukar maka da Alƙur'ani don ka wahala ba.

3. Sai don wa'azi ga wanda zai ji tsoron (haɗuwa da Allah).

4. Saukakke ne daga wanda Ya halicci ƙasa da sammai masu ɗaukaka.

5. (Allah) Mai rahama, Ya daidaita a kan Al'arshi.

6. Abin da yake sammai da ƙasa, da abin da yake tsakaninsu da kuma abin da yake ƙarƙashin ƙasa, (duka) nasa ne.

7. Idan kuma ka ɗaga murya da furuci to lalle Shi Yana sane da sirri da abin da ya fi (sirri) ɓuya.

8. Allah (Shi ne wanda) babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi; Yana da sunaye mafiya kyau.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori. Mun yi bayanin manufar buɗe wasu surori da irin waɗannan haruffa a farkon *Suratul Baƙara*.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabi Muhammad (ﷺ) cewa bai saukar masa da Alƙur'ani ba ne don ya wahalar da shi ta hanyar jefa shi cikin damuwa a kan mutanensa ba su yi imani da shi ba.
Allah ya saukar masa da Alƙur'ani ne don ya zama tunatarwa da wa'azi ga masu jin tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasu siffofi nasa da cewa, ban da saukar da Alƙur'ani, shi ne kuma ya halicci ƙasa da sammai bakwai maɗaukaka, kuma mai iko a kan komai da ke cikinsu. Kuma shi ne Allah mai rahama wanda ya daidaita a kan Al'arshinsa, daidaito wanda ya cancanta da shi.
Sannan ya siffanta kansa da cewa duk abin da yake cikin sammai da wanda yake bayan ƙasa da na ƙarƙashin ƙasa duk halittarsa ne shi kaɗai, kuma mulkinsa ne, bayinsa ne. Shi ne yake gudanar da su yadda ya ga dama.
Haka kuma ya bayyana faffaɗan iliminsa ga halittunsa inda ya nuna cewa, duk ɗaya ne a wurinsa, ko mutum ya ɗaga muryarsa yayin da yake magana ko ya sirranta ta, to shi Allah yana sane da maganar ta ɓoye da ma wadda ta fi ta ɓoyuwa; domin ya san sirrin da aka furta da ma wanda yake cikin zuciya ba a furta shi ba; hakanan ya san wanda ya ɗarsu a zuciya da ma wanda bai ɗarsu a cikinta ba. Watau dai iliminsa ya yalwaci komai babba da ƙarami na fili da na ɓoye.
Sai kuma ya tabbatar da Ɗayantakarsa wajen bauta, domin shi kaɗai ne abin bauta na gaskiya yana da kuma sunaye mafiya kyau da kamala.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da sigar tambaya ga Annabi Muhammadu (ﷺ) don jawo hankalin mai karatu da mai sauraro da nuna masa muhimmancin wannan labari da girmansa.

2. Wajabcin miji ya kula da iyalansa da lafiyarsu.

3. Matar mutum tana cikin ahalinsa.

4. Annabi Musa ya fito ne a lokacin tsananin sanyi haɗe da duhun dare, wannan ya sanya shi buƙatar samun garwashin wuta domin ɗumama jikinsu.

Suratu Ɗa Ha (9-10)

وَهَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰٓ ۝٩ إِذۡ رَءَا نَارٗا فَقَالَ لِأَهۡلِهِ ٱمۡكُثُوٓاْ إِنِّيٓ ءَانَسۡتُ نَارٗا لَّعَلِّيٓ ءَاتِيكُم مِّنۡهَا بِقَبَسٍ أَوۡ أَجِدُ عَلَى ٱلنَّارِ هُدٗى ۝١٠

9. Shin kuwa labarin Musa ya zo maka?

10. Lokacin da ya gano wuta sai ya ce da iyalinsa: “Ku zauna (a nan), lalle ni fa na hangi wuta, (zan je) ko na zo muku da garwashinta ko kuma in sami mai nuna mini (hanya) a wurin wutar.”

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tambayar Annabi (ﷺ) cewa ko labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo masa? Lokacin da Annabi Musa ya baro garin Madyana tare da matarsa domin komawa ƙasar haihuwarsa Masar bayan ya yi gudun hijira daga gare ta tsawon shekaru. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana cikin tafiya ne tare da iyalinsa sai ya ɓace hanya, ga kuma tsananin sanyi babu abin ɗumama jiki tare da su. Sai kawai ya hango wuta tana ci a gefen dutsen Ɗuri, sai ya sanar da iyalansa cewa, ya hango wani hasken wuta, su zauna zai je ya zo musu da garwashinta don ɗumama jiki, ko kuma ya sami wanda zai nuna masa hanya a wurin.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tafi neman garwashin wuta domin ɗumama jiki da ganin haske, sai kuma ga shi ya sami hasken shiriya, na wahayi mai haskaka zukata. Yana neman wanda zai nuna masa hanyar zuwa Masar, sai kuma ya sami shiriya zuwa hanya madaidaiciya, hanyar samun gidan Aljanna da yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Zaɓin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Musa da har ya yi magana da shi ya kuma ba shi manzanci wata babbar ni’ima ce da ya wajaba ya gode wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a kanta.

3. Ambaton Allah yana daga cikin manya-manyan manufofin shar’anta ibadu, saboda da shi ne zuciya take bautar Ubangiji take kuma natsuwa. Duk zuciyar da babu ambaton Allah tare da ita, to zuciya ce da babu wani alheri a cikinta. Babu kuma wata ibada da take tunatar da bawa Ubangijinsa kamar salla. Farkon wahayin da Allah ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ƙunshi shikashikan imani guda uku su ne: Tabbatar da Ɗayantakar Allah, watau Tauhidi da tabbatar da annabta da kuma tabbatar da tashin alƙiyama. Hakanan ya ƙunshi mafi girman ibada ta farilla, watau salla.

4. Gargaɗi game da duk wani mai ƙoƙarin yaɗa ɓarna da kira zuwa ga ƙarya da hana mutane yin imani na wajibi ko samun kamalar imaninsu, mai jefa ruɗani a cikin zukata. Wannan ya ƙunshi gargaɗi game da karanta littattafai masu gurɓata aƙida da lalata addini da wargaza imani.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci yin imani da shi da bauta masa da imani da ranar lahira, domin waɗannan abubuwa uku su ne shikashikan imani kuma rukunan addini; idan sun cika to addinin mutum ya cika, idan an sami tawaya a cikin ɗayansu ko a dukansu, to za a sami tawaya a cikin addinin mutum ko ma a rasa shi ɗungurungum.

Suratu Ɗa Ha (11-16)

فَلَمَّآ أَتَىٰهَا نُودِيَ يَٰمُوسَىٰٓ ﴿١١﴾ إِنِّيٓ أَنَا۠ رَبُّكَ فَٱخۡلَعۡ نَعۡلَيۡكَۖ إِنَّكَ بِٱلۡوَادِ ٱلۡمُقَدَّسِ طُوٗى ﴿١٢﴾ وَأَنَا ٱخۡتَرۡتُكَ فَٱسۡتَمِعۡ لِمَا يُوحَىٰٓ ﴿١٣﴾ إِنَّنِيٓ أَنَا ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدۡنِي وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِذِكۡرِيٓ ﴿١٤﴾ إِنَّ ٱلسَّاعَةَ ءَاتِيَةٌ أَكَادُ أُخۡفِيهَا لِتُجۡزَىٰ كُلُّ نَفۡسِۭ بِمَا تَسۡعَىٰ ﴿١٥﴾ فَلَا يَصُدَّنَّكَ عَنۡهَا مَن لَّا يُؤۡمِنُ بِهَا وَٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ فَتَرۡدَىٰ ﴿١٦﴾

11. To lokacin da ya zo wurinta (wato wutar), sai aka kira shi (cewa): “Ya Musa.

12. “Lalle Ni, Ni ne fa Ubangijinka, sai ka tuɓe takalmanka; lalle kana a tsarkakakken kwarin Ɗuwa ne.

13. “Kuma Ni Na zaɓe ka (da manzanci), sai ka ji abin da za a yiwo ma wahayi (da shi).

14. “Lalle Ni, Ni ne Allah, babu wani abin bauta sai Ni, to ka bauta mini, kuma ka tsai da salla don tuna Ni.

15. “Lalle alƙiyama za ta zo, ina nufin ɓoye ta ne don a saka wa kowanne rai da irin abin da yake aikatawa.

16. “To kada wanda bai yi imani da ita ba ya kuma bi son ransa ya hana ka gaskata ta, sai ka hallaka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin da Annabi Musa ya iso wurin wannan wutar da ya hango sai ya ga ashe wani gagarumin haske ne.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash’ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle Allah ba ya barci kuma bai kamata ya yi barci ba; yana yin ƙasa da ma’auni kuma yana yin sama da shi, ana ɗaga masa aikin dare kafin aikin rana, da aikin rana kafin na dare. Hijabinsa (shamakinsa) haske ne – a wata ruwayar ya ce ‘wuta ce’ – da ya yaye shi da hasken fuskarsa ya ƙona inda ganinsa ga halitta ya tuƙe.” [Muslim #179].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin da Annabi Musa ya iso wajen wannan wutar sai ya ji an kirawo sunansa Musa, a nan ya ji Allah yana tabbatar masa da cewa, shi ne (Allah) Ubangijinsa, don haka ya umarce shi da ya kwaɓe takalmansa domin yana wani kwari ne mai tsarki da ake kira Ɗuwa.
Allah ya ci gaba da sanar da Annabinsa cewa ya zaɓe shi a cikin mutane domin ya yi magana da shi ya kuma ba shi manzanci, don haka ya umarce shi da ya saurari abin da za a yi masa wahayi da shi.
Allah ya bayyana masa cewa shi ne Allah wanda babu wani abin bauta da gaskiya sai shi, ya umarce shi da ya bauta masa ya kuma tsayar da salla don ambatonsa da tunawa da shi.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wanda ya manta wata salla, to ya sallace ta lokacin da ya tuna ta, ba ta da wata kaffara sai hakan. ‘Kuma ka tsai da salla don tuna ni’.” [Bukhari #597 da Muslim #684].

Allah ya kuma tabbatar masa cewa, lalle alƙiyama gaskiya ce kuma tana nan tafe; ya ɓoye sanin lokacin da za ta zo, babu wanda ya san shi sai shi kaɗai. Kuma ya bayyana hikimar da ke cikin tashin mutane a ranar alƙiyama, shi ne don a yi wa kowa sakamako a kan abin da ya aikata mai kyau da marar kyau. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗe shi da cewa kada ya daka ta duk wani wanda bai yi imani da ranar lahira ba ya kuma bi son zuciyarsa don zai hana shi tunawa da wannan rana da kuma yin aiki domin tanadin zuwanta. Idan kuwa har ya yarda ya bi shi to zai hallaka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kyawawan ɗabi’un Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka sanya ya zama mai kyautatawa da kula da dabbobi ma. Wannan yana nuna irin tarbiyyar da Ubangiji ya yi masa domin ya zaɓe shi ya ɗora masa wani babban aiki na kira zuwa ga Allah da kula da Banu Isra’ila.

2. Kyakkyawan ladabi na Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa tambaya game da abin da yake hannunsa, wadda amsar wannan tambaya tana iya ɗaukan bayanin ainihin abin da yake ɗauke da shi, watau sanda, tana kuma iya ɗaukan bayanin amfaninta, sai ya faɗi duk abubuwan biyu: Ya ce sandarsa ce, kuma ya faɗi amfaninta a wurinsa.

3. Karfin imanin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Duk da cewa ya tsorata lokacin da sandarsa ta zama macijiya tana gudu, amma da Allah ya umarce shi ya dawo ya ɗauke ta, zai mayar da ita yadda take da farko, bai yi wata-wata ba nan take ya dawo ya ɗauke ta.

Suratu Ɗa Ha (17-24)

وَمَا تِلْكَ بِيَمِينِكَ يَٰمُوسَىٰ ﴿١٧﴾ قَالَ هِيَ عَصَايَ أَتَوَكَّؤُاْ عَلَيْهَا وَأَهُشُّ بِهَا عَلَىٰ غَنَمِي وَلِيَ فِيهَا مَارِبُ أُخْرَىٰ ﴿١٨﴾ قَالَ أَلْقِهَا يَٰمُوسَىٰ ﴿١٩﴾ فَأَلْقَىٰهَا فَإِذَا هِيَ حَيَّةٌ تَسْعَىٰ ﴿٢٠﴾ قَالَ خُذْهَا وَلَا تَخَفْ ۖ سَنُعِيدُهَا سِيرَتَهَا ٱلْأُولَىٰ ﴿٢١﴾ وَٱضْمُمْ يَدَكَ إِلَىٰ جَنَاحِكَ تَخْرُجْ بَيْضَآءَ مِنْ غَيْرِ سُوٓءٍ ءَايَةً أُخْرَىٰ ﴿٢٢﴾ لِنُرِيَكَ مِنْ ءَايَٰتِنَا ٱلْكُبْرَى ﴿٢٣﴾ ٱذْهَبْ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ﴿٢٤﴾

17. “Mene ne kuma wancan yake a hannun damanka ya Musa?”

18. (Musa) ya ce: “Ai sandata ce da nake jingina a kanta, ina kuma kaɗo wa dabbobina ganye da ita, ina kuma da sauran wasu buƙatu game da ita.”

19. (Allah) Ya ce: “Jefar da ita ya Musa.”

20. Sai ya jefar da ita, sai ga ta ta zama macijiya tana ta sauri.

21. Ya ce: “Kama ta, kuma kada ka ji tsoro; za Mu mai da ita kamar yadda take a da.

22. “Kuma ka haɗa hannunka da kwiɓinka zai fito fari sal ba tare da wata cuta ba; (wannan) wata ayar ce daban.

23. “Domin Mu nuna maka irin manya-manyan ayoyinmu.

24. “Ka tafi wurin Fir’auna don kuwa lalle ya ƙetare iyaka.”

A waɗannan ayoyi, bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ginshiƙan imani, watau imani da shi da kuma imani da ranar lahira, sai kuma ya nuna masa wasu ayoyinsa domin zuciyarsa ta ƙara natsuwa, ya ƙara tabbatarwa da cewa shi Manzon Allah ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye shi abin da yake a hannun ɗamarsa, tare da cewa ya fi kowa sanin ko mene ne, don ya jawo hankalinsa ya kuma nuna masa muhimmancin abin da zai nuna masa. Annabi Musa ya amsa wa Allah da cewa sandarsa ce a hannunsa, ya kuma faɗi wasu amfanunnuka guda biyu, amfani na farko ya shafe shi kai-tsaye, watau jingina da ita, na biyu kuwa ya shafi dabbobinsa, shi ne kakkaɓo musu ganyen da suke ci daga itatuwa masu tsawo. Sannan ya ƙara da cewa sandar har ila yau tana da wasu amfanuka na daban ban da waɗanda ya faɗa.
Sai Allah ya umarce shi da ya jefar da wannan sandar. Yana jefar da ita kuwa sai nan take ta zama babbar macijiya tana gudu a ƙasa. Ganin haka sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tsorata shi ma ya juya da baya a guje. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya tsaya ya daina gudu ya dawo ya ɗauki sandarsa, ya tabbatar masa cewa zai mayar da ita sanda kamar yadda take a da. Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya miƙa wuya ga umarnin Allah ya kuma ɗauki macijiyan nan, sai ga shi ta koma sanda kamar yadda take da farko.
Bayan wannan mu’ujizar kuma sai Allah ya nuna wa Musa wata mu’ujiza ta biyu, ita ce ya umarce shi da ya shigar da hannunsa na dama ta wuyan rigarsa ya haɗa shi da kwiɓinsa sannan ya fito da shi, zai fito yana haske fari ƙal kamar fitila, hasken kuma ba irin na wata cuta ba, kamar cutar albaras.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya yi haka ne don ya nuna masa wasu daga cikin manya-manyan ayoyinsa waɗanda za su ƙara tabbatar masa gaskiyar manzancinsa, ya kuma ƙara samun nutsuwa a zuciyarsa, su kuma zama hujjarsa a gaban Fir’auna da mutanensa.
Sai Allah ya umarce shi da ya tafi wurin Fir’auna Sarkin Masar ya kirawo shi zuwa ga gaskiya domin kuwa ya wuce iyaka da kafircinsa da zalunci da ɓarna a bayan ƙasa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wannan addu’a ta Annabi Musa tana nuna cikakken sanin da ya yi wa Allah da sanin yadda al’amura suke. Domin duk wani mai kira zuwa ga Allah idan aka neme shi da ya kirawo wani babba mai girman kai da zaƙewa wajen zalunci, to babu shakka zai buƙaci yalwar ƙirji da juriya da haƙuri, saboda cutarwa da zai iya fuskanta da baki ko a aikace. Zai kuma buƙaci fasahar harshe da azancin magana ta yadda hujjojinsa za su fito sarai a fahimce su, kuma ya iya ɓata duk wani ruɗani da ƙarya ta kowane maƙaryaci, kowa ya fahimta sarai. Hakanan zai buƙaci sanin ta inda ya kamata ya ɓullo wa al’amura, ya yi kira da hikima da kyakkyawan wa’azi. Haka kuma, zai buƙaci mataimaka waɗanda za su tallafa masa a kan aikinsa har ya yi nasara.

2. Falalar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bisa ga ɗan’uwansa Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), domin shi ne ya roƙa masa annabci kuma aka ba shi. Shi ya sa wasu malamai suka ce babu wani ɗan’uwa da ya kyautata wa ɗan’uwansa a duniya kamar yadda Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kyautata wa ɗan’uwansa Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

3. Hannu ɗaya ba ya ɗaukar jinka; don haka annabawa ma suna buƙatar mataimaka a cikin ayyukan da Allah ya ɗora musu na isar da saƙonsa. Babu wani annabi da ya sami mataimaka a kan aikin isar da saƙon Allah kamar yadda Annabi Muhammad (ﷺ) ya samu, su ne sahabbansa masu girma.

4. Ambaton Allah da yawa shi ne babban guzuri da duk wani mai kira zuwa ga Allah yake buƙata domin samun taimako da nasara daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Ɗa Ha (25-36)

قَالَ رَبِّ ٱشۡرَحۡ لِي صَدۡرِي ٢٥ وَيَسِّرۡ لِيٓ أَمۡرِي ٢٦ وَٱحۡلُلۡ عُقۡدَةٗ مِّن لِّسَانِي ٢٧ يَفۡقَهُواْ قَوۡلِي ٢٨ وَٱجۡعَل لِّي وَزِيرٗا مِّنۡ أَهۡلِي ٢٩ هَٰرُونَ أَخِي ٣٠
ٱشۡدُدۡ بِهِۦٓ أَزۡرِي ٣١ وَأَشۡرِكۡهُ فِيٓ أَمۡرِي ٣٢ كَيۡ نُسَبِّحَكَ كَثِيرٗا ٣٣ وَنَذۡكُرَكَ كَثِيرًا ٣٤ إِنَّكَ كُنتَ بِنَا بَصِيرٗا ٣٥ قَالَ قَدۡ أُوتِيتَ سُؤۡلَكَ
يَٰمُوسَىٰ ٣٦

25. (Musa) ya ce: “Ubangijina Ka buɗe mini ƙirjina.

26. “Kuma Ka sauƙaƙa mini lamarina.

27. “Ka kuma warware ƙullin da yake a harshena.

28. “(Don) su fahimci maganata.

29. “Kuma Ka sanya mini waziri daga dangina.

30. “(Watau) ɗau’uwana Haruna.

31. “Ka ƙarfafa gwiwata da shi.

32. “Kuma Ka shigar da shi cikin lamarina.

33. “Domin mu tsarkake Ka da yawa.

34. “Mu kuma ambace Ka da yawa.

35. “Lalle Kai Ka kasance Kana ganin mu.”

36. (Allah) Ya ce: “Haƙiƙa an ba ka abin da ka tambaya, ya Musa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana da shi ya kuma umarce shi da ya tafi Masar wajen Fir’auna wanda ya yi nisa cikin kafirci, har ma ya yi da’awar shi ubangiji ne abin bauta, sannan kuma ga shi babban azzalumi wanda ba abin da yake yi sai bautar da Banu Isra’ila yana kashe ‘ya’yansu maza yana bautar da matansu.
Da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fahimci girman aikin da aka ɗora masa sai ya roƙi Allah wasu buƙatu waɗanda za su taimaka masa ya samu sauke wannan nauyi da Allah ya ɗora masa.
Na farko, ya roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yalwata ƙirjinsa, ta yadda zai jure wa duk wani cin-kashi da Fir’auna da mutanensa za su yi masa. Domin har idan ƙirjinsa zai ƙuntata da maganganunsu ko ayyukansu, to zai kasa sauke nauyin da aka ɗora masa.
Na biyu, ya roƙe shi ya sauƙaƙa masa lamarinsa, watau ya kawar masa da duk wasu wahalhalu da masibu da ke cikin wannan aiki, ta yadda zai riƙa samun mafita a duk hanyar da ya bi, ya kuma samu karɓuwa a wurin mutanensa cikin sauƙi.

Na uku, ya roƙe shi ya warware masa ƙullin da yake kan harshensa, watau ya cire masa in'ina da take damun sa, ta yadda idan yana magana kowa zai fahimce shi cikin sauƙi.
Na huɗu, ya roƙe shi ya haɗa shi da wani mataimaki daga cikin danginsa, ya ayyana sunan ɗan'uwansa Haruna a matsayin wanda yake buƙatar a haɗa su tare wajen zartar da wannan babban aiki. Ya bayyana cewa yana son Allah ya ƙarfafa masa gwiwa da wannan ɗan'uwa nasa, ya kuma shigar da shi cikin lamarinsa, watau shi ma ya ba shi annabta ya aika su tare.
Sai Annabi Musa ya bayyana amfanin wannan buƙata tasa, da cewa, ya buƙaci haka ne don su haɗu wajen tsarkake Allah da yawa da ambaton sa da yawa, domin Allah yana ganin su ya san kuma halin da suke ciki na rauni da buƙatar duk abubuwan da ya roƙa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa ya amsa duk addu'o'insa, ya biya masa duk buƙatunsa da ya nema.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya so da rahamarsa ya kuma ba shi kulawarsa, to babu abin da zai cutar da shi ko ya hana rahamar Allah ta kai gare shi.

2. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya so bawansa, to yakan jefa soyayyarsa a cikin zukatan bayinsa, wani lokaci ma har da maƙiyansa.

3. Bayin Allah na ƙwarai sukan miƙa wuya ga umarnin Allah ko da kuwa a zahirinsa suna ganin akwai cutarwa a cikinsa, domin suna da tabbacin cewa Allah ba zai umarci bawansa da aikata wani abu da zai cutar da shi ba.

4. Bayanin tsananin son mahaifiya ga ɗanta.

Suratu Ɗa Ha (37-41)
وَلَقَدۡ مَنَنَّا عَلَيۡكَ مَرَّةً أُخۡرَىٰٓ ٣٧ إِذۡ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰٓ أُمِّكَ مَا يُوحَىٰٓ ٣٨ أَنِ ٱقۡذِفِيهِ فِي ٱلتَّابُوتِ فَٱقۡذِفِيهِ فِي ٱلۡيَمِّ فَلۡيُلۡقِهِ ٱلۡيَمُّ بِٱلسَّاحِلِ يَأۡخُذۡهُ عَدُوّٞ لِّي وَعَدُوّٞ لَّهُۥۚ وَأَلۡقَيۡتُ عَلَيۡكَ مَحَبَّةٗ مِّنِّي وَلِتُصۡنَعَ عَلَىٰ عَيۡنِيٓ ٣٩ إِذۡ تَمۡشِيٓ أُخۡتُكَ فَتَقُولُ هَلۡ أَدُلُّكُمۡ عَلَىٰ مَن يَكۡفُلُهُۥۖ فَرَجَعۡنَٰكَ إِلَىٰٓ أُمِّكَ كَيۡ تَقَرَّ عَيۡنُهَا وَلَا تَحۡزَنَۚ وَقَتَلۡتَ نَفۡسٗا فَنَجَّيۡنَٰكَ مِنَ ٱلۡغَمِّ وَفَتَنَّٰكَ فُتُونٗاۚ فَلَبِثۡتَ سِنِينَ فِيٓ أَهۡلِ مَدۡيَنَ ثُمَّ جِئۡتَ عَلَىٰ قَدَرٖ يَٰمُوسَىٰ ٤٠ وَٱصۡطَنَعۡتُكَ لِنَفۡسِي ٤١

37. "Haƙiƙa kuma Mun yi ni'ima a gare ka a wani lokaci.

38. "Sanda Muka yiwo wahayi ga mahaifiyarka da abin da ake yin wahayi da shi.

39. "Cewa, 'ki saka shi (jinjirin) a cikin akwatu, sannan ki jefa shi cikin kogi, to sai kogin ya jefa shi a gaba, sai maƙiyina kuma maƙiyinsa ya ɗauke shi.' Na kuma sanya maka farin jini daga gare Ni, don kuma a yi tarbiyar ka a gaban idona.

40. "Lokacin da 'yar'uwarka take tafiya tana cewa (da su): 'Yanzu ba na haɗa ku da wadda za ta raine shi ba?' Sai Muka komo da kai zuwa ga mahaifiyarka don zuciyarta ta yi sanyi, kada kuma ta yi baƙin ciki. Kuma ka kashe wani mutum sannan Muka tserar da kai daga uƙuba, Muka kuma jarrabe ka da jarrabobi daban-daban. Sannan ka zauna shekaru a cikin mutanen Madyana, sannan ka zo (nan) daidai lokacin da Na ƙaddarta (maka annabta) ya Musa.

41. “Kuma Na zaɓe ka don kaina.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wasu ni’imomi da ya yi masa a can baya. Ya lissafa ni’imomi takwas a nan:
Ta ɗaya, ya tunatar da shi lokacin da mahaifiyarsa ta haife shi a lokacin Fir’auna yana tsakiyar kashe jarirai maza, don haka ta tsorata matuƙa, sai Allah ya yi mata wahayi da cewa, ta saka shi cikin akwati ta jefa shi cikin ruwa. Sai ta yi hakan, ruwan kuma ya jefo shi a gaɓa, Fir’auna ya ɗauke shi ya rene shi a gidansa har ya zama babban mutum.
Ta biyu, Allah ya sanya masa farin jini, kowa ya gan shi sai ya ji yana ƙaunar sa, har Fir’auna da matarsa su ma suka ƙaunace shi, don haka suka ci gaba da kula da shi sosai.
Ni’ima ta uku, Allah ya hukunta a gaban idonsa aka rene shi, tare da kulawarsa da kiyayewarsa.
Ta huɗu, ita ce lokacin da mahaifiyarsa ta shiga damuwar rashin ganin ɗanta da zamansa a gidan Fir’auna shi kaɗai, har saura ƙiris ta bayyana abin da yake zuciyarta, amma sai Allah ya ɗaure mata zuciyarta ya ba ta juriya. A daidai wannan lokacin sai Allah ya hana shi kama nonon kowace mace, har sai da ‘yar’uwarsa ta je fadar Fir’auna ta faɗa musu cewa akwai mai shayarwa da za ta shayar musu da shi idan suna buƙata. A nan ne aka ba wa mahaifiyarsa dama, ta zo ta ba shi nono ya karɓa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dawo mata da shi don hankalinta ya kwanta ta daina baƙin cikin rabuwa da shi.
Ta biyar, ita ce lokacin da ya girma yana yawo cikin gari sai ya gamu da wani Baƙibɗe yana zaluntar wani Ba’isra’ile, sai ya nemi taimakon Musa. Garin ƙoƙarin kuɓutar da shi sai ya kashe wannan Baƙibɗen, don haka ya ji tsoro ya gudu zuwa garin Madyana. Allah ya tserar da shi daga fushin Fir’auna da uƙubarsa, ya kuma gafarta masa kuskuren kashe rai.
Ta shida, ita ce Allah ya yi masa jarrabawa daban-daban; ya haɗu da masifu iri-iri, tun daga cikin mahaifiyarsa har lokacin da ta haife shi ta jefa shi ruwa, mutanen Fir’auna suka tsince shi, ya kuma yi kisan kai ya gudu, duk Allah ya sanya ya haye waɗannan jarrabobin.
Ta bakwai, ita ce zamansa a garin Madyana inda ya yi aikin ƙwadago har ya sami yin aure a dalilin haka, sannan ya baro garin daidai lokacin da Allah ya ƙaddara masa samun annabta. Lalle duk waɗannan abubuwa gamon-katari ne daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Ta takwas, ita ce zaɓin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa domin ya yi magana da shi, ya ba shi manzanci, ya kuma aike shi zuwa Fir’auna da mutanensa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Annabi Adamu da Annabi Musa sun haɗu sai Musa ya ce wa Adamu: “Shin kai ne wanda ka jefa mutane cikin wahala ka fitar da su daga Aljanna?” Sai Adamu ya ce: “Shin kai ne wanda Allah ya zaɓe ka da manzancinsa, ya zaɓe ka don kansa, ya kuma saukar maka da Attaura?” Sai ya ce: “E.” Sai Adamu ya ce: “Ba ka san abin da ya faru da ni an riga an rubuta mini shi ba tun kafin a halicce shi?” Sai Musa ya ce: “E.” Sai Adamu ya ƙure Musa da hujja.” [Bukhari #4736 da Muslim #2652].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin ambaton Allah domin neman taimako da agaji daga Ubangiji.

2. Tausasa harshe wajen kira zuwa ga Allah cikin hikima da kyakkyawan wa’azi, ko da kuwa wanda ake yi wa wa’azin ya kai matuƙa wajen saɓon Allah.

3. Tsoro na ɗabi’a bai saba wa dogaro ga Allah ba. Annabawa kansu sukan ji tsoron abin da a ɗabi’ance ana jin tsoron sa.

4. Yalwar jin Allah da ganinsa ga kowa da komai a ko’ina a kuma kowane lokaci.

5. Allah yana tare da bayinsa na ƙwarai yana kare su, yana kula da su.

Suratu Ɗa Ha (42-46)
ٱذۡهَبۡ أَنتَ وَأَخُوكَ بِـَٔايَٰتِي وَلَا تَنِيَا فِي ذِكۡرِي ٤٢ ٱذۡهَبَآ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ٤٣ فَقُولَا لَهُۥ قَوۡلٗا لَّيِّنٗا لَّعَلَّهُۥ يَتَذَكَّرُ أَوۡ يَخۡشَىٰ ٤٤ قَالَا رَبَّنَآ إِنَّنَا نَخَافُ أَن يَفۡرُطَ عَلَيۡنَآ أَوۡ أَن يَطۡغَىٰ ٤٥ قَالَ لَا تَخَافَآۖ إِنَّنِي مَعَكُمَآ أَسۡمَعُ وَأَرَىٰ ٤٦

42. “Ka tafi kai da ɗan’uwanka da ayoyina, kada kuwa ku sassauta game da ambatona.

43. “Ku tafi wurin Fir’auna, don ko lalle ya wuce iyaka.

44. “Sai ku gaya masa magana mai taushi, ko wataƙila zai wa’azantu ko kuma ya ji tsoron (azabar Allah).”

45. (Musa da Haruna) suka ce: “Ya Ubangijinmu, lalle mu muna tsoron ya far mana ko kuma ya wuce iyaka (wajen yi mana uƙuba).”

46. Ya ce: “Kada ku ji tsoro; haƙiƙa Ni ina tare da ku, ina ji kuma ina ganin (komai).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da ya ba wa Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ɗan’uwansa Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) annabci sai ya umarce su da su tafi zuwa ga Fir’auna wanda ya ƙetare haddi wajen kafirci, har ma ya yi da’awar allantaka, ya kuma gawurta matuƙa wajen zalunci. Allah kuma ya ba wa Musa da ɗan’uwansa Haruna mu’ujizoji waɗanda za su tabbatar wa da Fir’auna da mutanensa gaskiyarsu, ya kuma umarce su da cewa kada su yi rauni wajen ambatonsa a kai-a kai, domin su cika alƙawarin da suka ɗauka na cewa za su ambace shi tare da tsarkake shi da yawa.
Allah kuma ya umarce su da su fara bin hanyar hikima wajen kiran Fir’auna; su yi masa magana mai taushi cikin ladabi ba tare da kausasa harshe ba. Ya nuna musu amfanin yin hakan, shi ne don jawo hankalin Fir’auna, wataƙila ya wa’azantu daga abin da za su faɗa masa, ya gane amfaninsa a gare shi, ko kuma ya tsorata ya bar miyagun ayyukansa don jin tsoron abin da zai same shi na azaba idan ya bijire wa wa’azinsu.
Sai Annabi Musa da Haruna suka nuna wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) abin da suke tsoron ya faru lokacin da za su tsaya gaban Fir’auna don su yi masa wa’azi, suka nuna suna jin tsoron ya far musu da cutarwa da uƙuba tun gabanin ma su gama isar masa da saƙon Allah, ko kuma bayan sun isar masa ya ji amma ya yi taurin kai ya bijire.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa musu cewa kada su ji tsoron komai daga Fir’auna, ba zai iya far musu ba, domin Allah yana tare da su yana ba su kariya kuma yana sane da duk abin da yake wakana, yana kuma ganin halin da suke ciki. Daga nan Annabi Musa da ɗan’uwansa Haruna suka sami nutsuwa suka daina jin wani tsoro.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayan kira zuwa ga kaɗaita Allah da bauta, manzanni sun zo domin ceton raunana daga hannun azzalumai.

2. Babu mai samun kuɓuta daga azabar Allah sai wanda ya bi shiriyar da annabawa suka zo da ita.

Suratu Ɗa Ha (47-48)

فَأۡتِيَاهُ فَقُولَآ إِنَّا رَسُولَا رَبِّكَ فَأَرۡسِلۡ مَعَنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ وَلَا تُعَذِّبۡهُمۡۖ قَدۡ جِئۡنَٰكَ بِـَٔايَةٖ مِّن رَّبِّكَۖ وَٱلسَّلَٰمُ عَلَىٰ مَنِ ٱتَّبَعَ ٱلۡهُدَىٰٓ ٤٧ إِنَّا قَدۡ أُوحِيَ إِلَيۡنَآ أَنَّ ٱلۡعَذَابَ عَلَىٰ مَن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ٤٨

47. “Sai ku tafi wajensa sannan ku ce (da shi): “Lalle mu manzannin Ubangijinka ne, sai ka sakar mana Banu-Isra’ila, kada kuma ka azabtar da su; haƙiƙa mun zo maka da aya daga Ubangijinka; aminci kuwa ya tabbata ga wanda ya bi shiriya.

48. “Lalle mu an yi mana wahayi cewa, ita azaba lalle tana nan ga wanda ya ƙaryata ya kuma ba da baya.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ɗan’uwansa Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa su tafi wajen Fir’auna su isar masa saƙon da Allah ya aike su da shi. Ya umarce su da abubuwa biyu: Na farko, su kira Fir’auna zuwa ga Musulunci. Na biyu, su ceto Banu Isra’ila daga azaba da bautar da Fir’auna ya jefa su a cikinta shekara da shekaru, domin su ma su sami ‘yanci, ya kuma tsayar musu da Shari’ar Allah.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Abu Sufyana ya faɗa masa cewa lokacin da Hiraƙlu Sarkin Rumawa ya kirawo shi tare da wasu Kuraishawa ‘yan kasuwa ya yi umarni a ɗauko wasiƙar da Manzon Allah (ﷺ) ya rubuta masa, a cikinta yana ce masa: “Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai. Daga Muhammadu bawan Allah kuma Manzonsa zuwa ga Hiraƙlu Shugaban Rumawa, aminci ya tabbata ga wanda ya bi shiriya...” [Bukhari #6260 da Muslim #1773].

Annabi Musa ya bayyana wa Fir’auna cewa sun zo masa da wasu ayoyi guda biyu, watau mu’ujizar sanda mai zama macijiya da hannu mai haske da Allah ya ba shi. Ya kuma bayyana masa cewa babu mai samun kuɓuta a duniya da lahira sai wanda ya bi Shari’ar Allah ya rungumi shiriya hannu bibbiyu. Suka tabbatar wa da Fir’auna cewa su manzannin Allah ne da ya yi wa wahayi ya aiko su da saƙon cewa duk wanda ya ƙaryata abin da manzanni suka zo da shi daga Allah, ya bijire wa gaskiya, to azaba ta tabbata gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wata halitta da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi, to sai ya nuna mata abin da yake maslaha gare ta, don haka ne kowace halitta take neman abin da zai amfane ta, take kuma guje wa abin da zai cutar da ita. Wannan ita ce shiriyar Allah ta bai-ɗaya wadda ta shafi kowace irin halitta da Allah ya yi. Amma keɓantacciyar shiriya, watau shiryarwa zuwa ga imani da Allah da manzanninsa, wannan ta keɓanta ne kawai ga waɗanda Allah ya zaɓa.

2. Ilimin Allah cikakke ne ba shi da tawaya ta ko’ina, domin shi ilimi ne da jahilci bai gabace shi ba, kuma mantuwa ba za ta riske shi ba.

3. Fitar da tsirrai da shuke-shuke iri-iri dalili ne da yake nuna cikakkiyar Kudurar Allah da samuwarsa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya ambaci dalilai na hankali guda biyu waɗanda suke tabbatar da yiwuwar sake tashin halittu bayan mutuwarsu; su ne fito da tsirrai daga ƙasa bayan mutuwarta da halittar jinsin ɗan’adam daga gare ta.

Suratu Ɗa Ha (49-55)

قَالَ فَمَن رَّبُّكُمَا يَٰمُوسَىٰ ﴿٤٩﴾ قَالَ رَبُّنَا ٱلَّذِىٓ أَعۡطَىٰ كُلَّ شَىۡءٍ خَلۡقَهُۥ ثُمَّ هَدَىٰ ﴿٥٠﴾ قَالَ فَمَا بَالُ ٱلۡقُرُونِ ٱلۡأُولَىٰ ﴿٥١﴾ قَالَ عِلۡمُهَا عِندَ رَبِّى فِى كِتَٰبٍ لَّا يَضِلُّ رَبِّى وَلَا يَنسَى ﴿٥٢﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ مَهۡدًا وَسَلَكَ لَكُمۡ فِيهَا سُبُلًا وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخۡرَجۡنَا بِهِۦٓ أَزۡوَٰجًا مِّن نَّبَاتٍ شَتَّىٰ ﴿٥٣﴾ كُلُواْ وَٱرۡعَوۡاْ أَنۡعَٰمَكُمۡ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٍ لِّأُوْلِى ٱلنُّهَىٰ ﴿٥٤﴾ ۞ مِنۡهَا خَلَقۡنَٰكُمۡ وَفِيهَا نُعِيدُكُمۡ وَمِنۡهَا نُخۡرِجُكُمۡ تَارَةً أُخۡرَىٰ ﴿٥٥﴾

49. (Fir’auna) ya ce: “Wane ne Ubangijin naku ya Musa?”

50. (Musa) ya ce: “Ubangijinmu (Shi ne) Wanda Ya bai wa kowane abu surar halittarsa sannan Ya shiryar (da shi yadda zai yi tasarrufi).”

51. (Fir’auna) ya ce: “To mene ne halin da al’ummun farko suke ciki?”

52. (Musa) ya ce: “Saninsu yana wurin Ubangijina a cikin Lauhul-Mahafuzu; Ubangijina kuma ba Ya kuskure (cikin iliminsa) kuma ba Ya mantuwa.

53. “(Shi ne) Wanda Ya sanya muku ƙasa a shimfiɗe, Ya kuma sanya muku hanyoyi na tafiya cikinta, kuma Ya saukar da ruwa daga sama”, sannan Muka fitar da dangogin shuke-shuke iri-iri da shi (ruwa).

54. Ku ci (daga tsirran) kuma ku yi kiwon dabbobinku. Lalle a game da wannan akwai ayoyi ga ma’abota hankula.

55. Daga ita (ƙasar) Muka halicce ku, kuma a cikinta za Mu mayar da ku, daga ita kuma za Mu fito da ku a wani karon.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da labarta abin da ya faru tsakanin Annabi Musa da ɗan’uwansa Haruna da kuma Fir’auna, yayin da suka kira shi ya ba da gaskiya da Allah shi kaɗai, sai ya shiga nuna musu rashin yardarsa da samuwar Allah, har yake tambayar su cewa, wane ne ma Ubangijinsu wanda suke cewa shi ne ya aiko su? Sai Annabi Musa ya amsa masa da cewa, shi ne wanda ya ba wa kowanne abu da ya halitta surar halittarsa da kamanninsa da ya dace da shi, sannan ya shiryar da ɗaukacin halittunsa ga abin da ya halitta dominsu.
Da Fir’auna ya tabbatar ba zai iya rushe hujjar Annabi Musa ba, sai nan take ya canja salon tambayarsa ya koma yana kafa hujja da al'ummun da suka gabata waɗanda suka aikata kafirci cewa, su kuma me suke ciki, tun da ba su bauta wa Allah ba, sun bauta wa wasu abubuwa daban? Sai Annabi Musa ya nuna masa cewa waɗannan al'ummun, duk da cewa ba su bauta wa Allah ba, to amma Allah ya ƙididdige ayyukansu da suka yi suna nan a wurinsa a rubuce a littafin Lauhul Mahfuzu, babu abin da iliminsa yake kuɓuce masa, ya san komai babba da ƙarami, kuma ba ya manta duk wani abu da ya sani.
Sai kuma Annabi Musa ya ci gaba da faɗa wa Fir’auna siffofin Allah, da cewa, Allah shi ne wanda ya halitta musu ƙasa a shimfiɗe domin su ji daɗin rayuwa da tafiya a kanta, ya kuma sanya musu hanyoyin tafiya a kanta zuwa duk inda suke buƙata su je, ya saukar musu da ruwan sama wanda da shi ne ya fitar musu da shuke-shuke iri-iri. Ya umarce su da su ci daga abin da ya fitar musu daga ƙasa na halal masu daɗi, su kuma ciyar da dabbobinsu irin abincinsu. Sai Allah ya bayyana cewa a cikin waɗannan ni’imomi

da ya yi musu ba shakka akwai tarin ayoyi da dalilai masu nuna Kudurar Allah da Kaɗaitakarsa ga mutane masu hankali.
Sai kuma ya ci gaba da cewa, wannan ƙasar dai mai fitar musu da abincinsu da na dabbobinsu, da ita ne ya halicci mutane, halittar asalinsu, watau Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), mutum na farko da Allah ya halicce shi daga ƙasa. Ya kuma bayyana cewa, bayan sun mutu a cikin ƙasar dai za a binne su, sannan idan lokacin tashin alƙiyama ya zo daga cikinta ne za a fito da su domin tattara su a yi musu hisabi a kan ayyukan da suka gabatar a nan duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba rashin samun gamsasshiyar hujja ce ya hana Fir'auna ba da gaskiya ba, Allah ya nuna masa hujjoji masu yawa ya kuma gan su da idanunsa ya fahimce su, amma saboda girman kai da nuna isa ya bijire ya ƙi yin imani.

2. Fir'auna ya san irin yadda mutane suke son ƙasarsu, suke kuma ƙin yarda a kore su daga cikinta ko wasu su zo su ƙwace musu mulkin ƙasarsu. Sai ya yi amfani da wannan damar ya bayyana Annabi Musa da cewa shi ne wanda ya zo domin ya kore su daga ƙasarsu ya ƙwace mulki daga hannunsu. Wannan shi zai sa su tsane shi su ba wa Fir'auna haɗin kai wajen yaƙar sa.

3. Annabi Musa ya zaɓi ranar idi ta zama ranar haɗuwa da matsafan Fir'auna, domin ita ce ranar da mutane sukan bar duk harkokinsu, sukan tattaru wuri guda ; wannan zai ba su damar halartar wurin wannan haɗuwar domin su gane wa idanuwansu duk abin da zai faru, sannan labarin zai watsu ko'ina da ina cikin gaggawa.

4. Duk wanda zai goya wa wani baya, ya kuma yi amfani da shi wajen faɗa da gaskiya da cutar da masu gaskiya, to ƙarshensa taɓewa da hasara duniya da lahira.

Suratu Ɗa Ha (56-61)

وَلَقَدۡ أَرَيۡنَٰهُ ءَايَٰتِنَا كُلَّهَا فَكَذَّبَ وَأَبَىٰ ٥٦ قَالَ أَجِئۡتَنَا لِتُخۡرِجَنَا مِنۡ أَرۡضِنَا بِسِحۡرِكَ يَٰمُوسَىٰ ٥٧ فَلَنَأۡتِيَنَّكَ بِسِحۡرٖ مِّثۡلِهِۦ فَٱجۡعَلۡ بَيۡنَنَا
وَبَيۡنَكَ مَوۡعِدٗا لَّا نُخۡلِفُهُۥ نَحۡنُ وَلَآ أَنتَ مَكَانٗا سُوٗى ٥٨ قَالَ مَوۡعِدُكُمۡ يَوۡمُ ٱلزِّينَةِ وَأَن يُحۡشَرَ ٱلنَّاسُ ضُحٗى ٥٩ فَتَوَلَّىٰ فِرۡعَوۡنُ فَجَمَعَ كَيۡدَهُۥ
ثُمَّ أَتَىٰ ٦٠ قَالَ لَهُم مُّوسَىٰ وَيۡلَكُمۡ لَا تَفۡتَرُواْ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبٗا فَيُسۡحِتَكُم بِعَذَابٖۖ وَقَدۡ خَابَ مَنِ ٱفۡتَرَىٰ ٦١

56. Kuma haƙiƙa Mun nuna masa (Fir'auna) ayoyinmu dukkansu, sai ya ƙaryata kuma ya ƙi (ba da gaskiya).

57. (Fir'auna) ya ce: "Yanzu ka zo mana ne don ka fitar da mu daga ƙasarmu da sihirinka, ya Musa?

58. "To lalle kuwa za mu zo maka da wani sihirin irinsa; sai ka sanya lokaci na musamman tsakaninmu da kai wanda mu ba za mu saɓa masa ba, kai ma haka, (ya zama) wuri ne tsaka-tsaki"

59. (Musa) ya ce: "Lokacin (da na sanya) muku shi ne ranar idi, kuma a tattara mutane da hantsi."

60. Sai Fir'auna ya juya, sai ya haɗa makircinsa, sannan ya zo (wurin da aka shirya).

61. Musa ya ce da su: "Kaiconku! Kada fa ku ƙirƙira wa Allah ƙarya, sai Ya hallaka ku da azaba; haƙiƙa kuwa wanda ya ƙirƙira (masa ƙarya) to ya taɓe."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya nuna wa Fir’auna ayoyinsa da dama masu nuna Kaɗaitarsa amma wannan bai sa ya miƙa wuya ya ba da gaskiya ba. Sai ya bijire wa umarnin Allah da haninsa, ya ƙaryata hujjoji na gaskiya da ake faɗa masa, ya ƙi yin imani. Maimakon haka ma sai cewa yake yi wai Annabi Musa da man ya zo ne don ya kore su daga ƙasarsu ta Masar domin ya gaje mulkin Fir’auna ta hanyar amfani da tsafi. Har ma ya yi kurarin zai zo masa da wani tsafi irin nasa domin su kara, don haka ya nemi ya ɗan saurara masa, ya ba shi lokaci da wuri na musamman wanda shi da su za su haɗu a cikinsa, babu mai saɓawa, don a ga wanda tsafinsa zai fi tasiri.
Sai Annabi Musa ya sanya wa Fir’auna ranar idi ta zamanto ranar haɗuwarsu, ya kuma nemi a gayyato mutane gaba ɗaya su taru lokacin da suke gabatar da bukukuwan idinsu a lokacin hantsi, domin kowa ya gane wa idonsa yadda za ta kaya.
Sai nan da nan Fir’auna ya shirya ƙulle-ƙullen makircinsa, ya aika gari-gari aka gayyato masa manyan matsafa masu tarin yawa. Da ranar haɗuwa ta zo sai ya sanya aka yi wa mutane shelar su tattaro su halarci wurin da aka yi alƙawari. Mutane duk suka hallara maza da mata manya da yara daga ko’ina. Annabi Musa ya fara da yi wa matsafan nan wa’azi da cewa, su kiyayi yi wa Allah ƙarya domin kawai su yaudari mutane da tsafi su ɓatar da su. Idan kuwa suka yi haka Allah zai saukar musu da azabarsa wadda za ta hallaka su. Ya kuma tabbatar musu da cewa duk wanda ya ƙaga wa Allah ƙarya to ya taɓe ya yi hasara.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gaskiya ko yaya take, to za ta hargitsa ƙarya ta jefa maƙaryata cikin shakku da ɗimuwa. Kalmomin wa’azi da suka fito daga bakin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su suka sa matsafan Fir’auna duk suka gigice har suka shiga tabka mahawara da ganawa a asirce don gano mafita da neman hanyar murƙushe gaskiyar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Bayan tattaunawar matsafan game da hanyoyin tunkarar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba su iya kaiwa ga wani abu sabo ba sai tabbatar da abubuwan da Fir’auna ya riga ya faɗa a baya da nufin ɓata sunan Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a wurin mutane. Abubuwa uku ne:
Na farko, nuna wa mutane cewa Musa da Haruna ba annabawa ne ba, matsafa ne kawai. Mutane kuwa sun fahimci tsafi ba wani abin kirki ne ba, wannan zai sanya su ƙara ƙyamatar su.
Na biyu, buƙatarsu ita ce raba mutane da ƙasarsu, wannan kuwa abu ne da mutane ba za su taɓa yarda da shi ba.
Na uku, kawar wa da mutane kyakkyawar hanyar rayuwarsu, wanda ya haɗa da ƙwace musu mulki da raba su da muƙamansu da sana’o’insu. Yarda da hakan abu ne mai matuƙar wuya.

3. Matsafan Fir’auna sun fitar da tsarin da za su fuskanci Annabi Musa da ɗan’uwansa Haruna da shi, wanda ya ƙunshi abubuwa uku:
Na farko, su je su shirya sosai, su yi tsari na bai-ɗaya domin wannan zai ƙara musu ƙarfi.
Na biyu, su shigo filin daga kamar mayaƙa sahu-sahu; yin haka zai ƙara musu kwarjini da jefa tsoro a zukatan abokan hamayya.
Na uku, su riƙa tunawa da gwaggwabar kyautar da Fir’auna ya yi musu alƙawarin yi musu idan har sun yi nasara a kan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Tunanin samun wannan kyauta zai ƙara musu himma da jajircewa.

Suratu Ɗa Ha (62-64)

فَتَنَٰزَعُوٓاْ أَمۡرَهُم بَيۡنَهُمۡ وَأَسَرُّواْ ٱلنَّجۡوَىٰ ٦٢ قَالُوٓاْ إِنۡ هَٰذَٰنِ لَسَٰحِرَٰنِ يُرِيدَانِ أَن يُخۡرِجَاكُم مِّنۡ أَرۡضِكُم بِسِحۡرِهِمَا وَيَذۡهَبَا بِطَرِيقَتِكُمُ ٱلۡمُثۡلَىٰ ٦٣ فَأَجۡمِعُواْ كَيۡدَكُمۡ ثُمَّ ٱئۡتُواْ صَفّٗاۚ وَقَدۡ أَفۡلَحَ ٱلۡيَوۡمَ مَنِ ٱسۡتَعۡلَىٰ ٦٤

62. Sai suka tattauna al’amarinsu a tsakaninsu, suka kuma gana a asirce.

63. Suka ce: “Lalle waɗannan biyun (Musa da Haruna) tabbas matsafa ne, suna so ne su fitar da ku daga ƙasarku da tsafinsu, su kuma tafiyar da kyakkyawar hanyarku (ta rayuwa).

64. “Sai ku yiwo shiri haɗaɗɗe sannan ku zo sahu-sahu. Haƙiƙa yau kam wanda ya yi nasara ya rabuta!”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana lokacin da matsafa suka saurari wa’azin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai suka shiga tafka mahawara a tsakaninsu, suka kuma gana da junansu a asirce. Sai wasu matsafan suka faɗa wa ‘yan’uwansu cewa lalle Musa da Haruna su ma matsafa ne, kuma babbar manufarsu ita ce su yi amfani da tsafinsu su fitar da mutane daga ƙasar Masar, sannan su kawar musu da kyakkyawar hanyar rayuwarsu, domin su su tabbatar da tasu hanyar ta hanyar tsafi, daga nan sai su yi suna, su kuma matsafan tauraronsu ya disashe, hanyar cin abincinsu ta toshe. Don haka ne sai suka ƙara tunzura junansu, suka umarci juna da su koma su shirya su inganta lamarinsu na tsafi da makircinsu, sannan su fito sahu-sahu domin razanarwa da ba da tsoro da cika ido. Sai suka shirya sakin kayansu na tsafi a lokaci guda, suka kuma ba wa junansu tabbacin cewa a yau kam wanda ya yi galaba shi ne zai rabauta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matsafa sun ba wa Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zaɓin ya fara jefa sandarsa ko su su fara domin su nuna masa cewa za su yi masa adalci ba za su zalunce shi ba. Sannan suna ganin ko ta halin ƙaƙa su ne za su yi nasara.

2. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ba su damar su fara jefa nasu, domin su ƙure adakarsu, su gama iya bakin ƙoƙarinsu, daga baya ya zo da ayarsa don ta rusa tsafe-tsafensu.

3. Annabawa suna jin tsoro irin na ɗabi’a, don haka Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ji tsoron ganin igiyoyi da sanduna sun zama macizai suna ta yawo, duk kuwa da cewa ya tabbatar da Allah zai ba shi nasara a kansu.

4. Duk daga inda matsafi ya fito a duniya ba zai yi nasara ba, hakanan duk irin dabarun da zai yi amfani da su ba za su yi tasiri ba, domin ba zai cimma buƙatarsa ba mai kyau ko marar kyau.

5. Imani yakan haifar da abubuwan ban mamaki; dubi yadda imani ya ratsa zukatan matsafa ya kafu a cikinsu, don haka sai ba su ɗauki azabar duniya a bakin komai ba; barazanar Fir’auna ba ta yi musu kowane irin tasiri ba.

6. Al’ada ce ta azzaluman shugabanni a koyaushe su riƙa amfani da barazana da tsoratarwa domin cimma munanan muradansu.

7. Haka Allah yake zartar da ikonsa, cikin ɗan ƙanƙanin lokaci sai ya canja wani yanayi zuwa wani daban. Ga shi da safe suna matsafa kafirai, amma yamma na yi sai ga shi sun zama shahidai.

8. Shugabannin ɓata a koyaushe sukan raina hankalin jama'arsu ne, wannan ya sa Fir'auna ya zargi matsafansa da cewa sun haɗa baki da Annabi Musa har da cewa ma shi ne shugabansu, tare da cewa babu ta inda Annabi Musa ya haɗu da waɗannan matsafa; domin shi ya fito ne daga garin Madyana, kuma yana isowa Masar kai-tsaye ya tafi wajen Fir'auna ya yi masa wa'azi, ya nuna masa mu'ujizojin da Allah ya ba shi. Wannan ya sa Fir'auna ya yi umarni a tattaro masa manyan matsafa ƙwararru daga ko'ina, suka zo ya kuma yi musu alƙawarin lada mai tsoka da muƙamai da zai ba su idan har sun yi nasara a kan Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Su ma suka nuna za su yi iya bakin ƙoƙarinsu don su ga sun yi rinjaye a kansa. To da wannan abu ya auku sai ga Fir'auna yana irin waccan tuhuma ta haɗin baki marar kan gado ko tushe.

Suratu Ɗa Ha (65-73)

قَالُواْ يَٰمُوسَىٰٓ إِمَّآ أَن تُلۡقِيَ وَإِمَّآ أَن نَّكُونَ أَوَّلَ مَنۡ أَلۡقَىٰ ٦٥ قَالَ بَلۡ أَلۡقُواْۖ فَإِذَا حِبَالُهُمۡ وَعِصِيُّهُمۡ يُخَيَّلُ إِلَيۡهِ مِن سِحۡرِهِمۡ أَنَّهَا تَسۡعَىٰ ٦٦ فَأَوۡجَسَ فِي نَفۡسِهِۦ خِيفَةٗ مُّوسَىٰ ٦٧ قُلۡنَا لَا تَخَفۡ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡأَعۡلَىٰ ٦٨ وَأَلۡقِ مَا فِي يَمِينِكَ تَلۡقَفۡ مَا صَنَعُوٓاْۖ إِنَّمَا صَنَعُواْ كَيۡدُ سَٰحِرٖۖ وَلَا يُفۡلِحُ ٱلسَّاحِرُ حَيۡثُ أَتَىٰ ٦٩ فَأُلۡقِيَ ٱلسَّحَرَةُ سُجَّدٗا قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِرَبِّ هَٰرُونَ وَمُوسَىٰ ٧٠ قَالَ ءَامَنتُمۡ لَهُۥ قَبۡلَ أَنۡ ءَاذَنَ لَكُمۡۖ إِنَّهُۥ لَكَبِيرُكُمُ ٱلَّذِي عَلَّمَكُمُ ٱلسِّحۡرَۖ فَلَأُقَطِّعَنَّ أَيۡدِيَكُمۡ وَأَرۡجُلَكُم مِّنۡ خِلَٰفٖ وَلَأُصَلِّبَنَّكُمۡ فِي جُذُوعِ ٱلنَّخۡلِ وَلَتَعۡلَمُنَّ أَيُّنَآ أَشَدُّ عَذَابٗا وَأَبۡقَىٰ ٧١ قَالُواْ لَن نُّؤۡثِرَكَ عَلَىٰ مَا جَآءَنَا مِنَ ٱلۡبَيِّنَٰتِ وَٱلَّذِي فَطَرَنَاۖ فَٱقۡضِ مَآ أَنتَ قَاضٖۖ إِنَّمَا تَقۡضِي هَٰذِهِ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَآ ٧٢ إِنَّآ ءَامَنَّا بِرَبِّنَا لِيَغۡفِرَ لَنَا خَطَٰيَٰنَا وَمَآ أَكۡرَهۡتَنَا عَلَيۡهِ مِنَ ٱلسِّحۡرِۗ وَٱللَّهُ خَيۡرٞ وَأَبۡقَىٰٓ ٧٣

65. Suka ce: "Ya Musa, ko dai ka jefa (naka) ko kuma mu mu fara jefa (namu)."

66. Ya ce: "A'a, ku (fara) jefawa." To saboda sihirinsu sai ga igiyoyinsu da sandunansu ana suranta masa cewa su (macizai ne) suna sauri.

67. Sai Musa ya ɓoye (wani abu) na tsoro a ransa.

68. Muka ce: "Kada ka ji tsoro, lalle kai kake da rinjaye.

69. "Kuma ka jefar da abin da yake hannunka na dama, za ta haɗiye abin da suka aikata; lalle abin da suka aikata makircin matsafi ne; matsafi kuwa ba ya rabauta duk ta inda ya zo."

70. Sai matsafan suka faɗi suna sujjada suka ce: "Mun yi imani da Ubangijin Haruna da Musa!"

71. (Fir'auna) ya ce: "Yanzu kwa yi imani da shi tun kafin in yi muku izini? Lalle shi ne babbanku wanda ya koya muku tsafi; to lalle zan yayyanke hannayenku da ƙafafuwanku a tarnaƙe (wato hannun dama da ƙafar hagu), kuma tabbas zan gicciye ku a kan kututturen dabino, lalle kuma tabbas za ku san wane ne tsakanin ni da shi wanda ya fi tsananin azaba kuma ta fi ɗorewa.

72. Suka ce: "Ba za mu fifita ka ba a kan abin da ya zo mana na (ayoyi) mabayyana, da kuma a kan wanda Ya halicce mu. Sai ka hukunta duk abin da za ka hukunta; za ka yi hukunci ne kawai a wannnan rayuwar ta duniya.

73. “Lalle mu kam mun yi imani da Ubangijinmu don Ya gafarta mana laifukanmu da kuma abin da ka tilasta mu a kansa na tsafi. Allah kuwa Shi ne Mafi alherin (sakamako), kuma Shi ne Mafi dawwamar (azaba).”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da siffanta yadda matsafan Fir’auna suka shigo fili kamar yadda suka tsara, sai suka ba wa Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zaɓi, ko dai ya fara jefa sandarsa ko kuma su su fara jefa nasu sandunan da igiyoyi. Sai Annabi Musa ya ba su zaɓi kan su fara jefa nasu. Sai ko matsafan suka jefa sandunansu da igiyoyinsu na tsafi. Saboda sihirinsu sai aka suranta wa Annabi Musa cewa sun zama macizai suna ta sauri. Ganin haka sai Annabi Musa ya tsorata, amma sai ya ɓoye tsoronsa a ransa. Sai Allah ya kwantar masa da hankali da cewa kada ya ji tsoron abin da yake gani na sihirinsu, lalle shi ne zai yi nasara a kansu.
Sai kuma ya umarce shi da ya jefar da sandarsa za ta haɗiye dukkan igiyoyinsu da sandunansu waɗanda suka sihirce idanuwan mutane da su; ya tabbatar masa da cewa abin da suka yi makirci ne kawai na matsafa, kuma duk ta inda matsafi ya ɓullo ba zai yi nasara ba.
Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bi umarnin Ubangijinsa ya jefar da sandarsa, nan take kuwa sai ta juye ta zama macijiya ta kuma bi sandunansu da igiyoyinsu tana ta haɗiyewa. Da ganin haka sai matsafan suka faɗi gaba ɗaya suka yi sujjada domin sun fahimci abin da Musa ya zo da shi tabbas ba tsafi ne ba; wani abu ne daga Allah, suka ce: Mun yi imani da Ubangijin Musa da Haruna, shi ne kuma Ubangijin duk halittu.Sai Fir’auna saboda tsananin kafircinsa ya fara yi wa matsafan nan barazana da gargaɗi mai tsanani da cewa, don me suka yi imani ba tare da sun nemi izininsa ba? A ƙarshe kuma ya wayance ya juya zancen da cewa, ai Musa ne shugabansu, shi ne ma ya koya musu tsafi, don haka yanzu sun haɗa baki ne da shi don su fitar da mutane daga ƙasar Masar su ƙwace mulki. Saboda haka sai ya azabtar da su ta hanyar yanke musu hannayensu da ƙafafunsu a tarnaƙe, watau hannun dama da ƙafar hagu, sannan kuma lalle sai ya gicciye su a kan kututturen dabino; ya yi kurarin cewa tabbas za su fahimci tsakanin shi da Ubangijin Musa wane ne ya fi tsananin azaba kuma mafi ɗorewa?
Allah kuma ya bayyana mana cewa, duk wannan kurarin na Fir’auna bai razana matsafan nan ba balle har su janye imanin da suka yi da Allah Ta’ala, sai kawai suka ce masa lalle su kam ba za su fifita binsa a kan bin abin da ya zo musu na ayoyi bayyanannu ba, ba kuma za su fifita shi a kan Allah wanda ya halicce su ba. Suka nuna masa ya yi duk abin da yake ganin zai yi musu, domin ba shi da wani iko a kansu sai a wannan rayuwa ta duniya mai ƙarewa, kuma ikonsa mai gushewa ne ba zai tabbata ba. Suka ƙara tabbatar masa cewa su sun yi imani da Ubangijinsu suna kuma fatan ya yafe musu laifin kafircinsu da sauran laifuffukansu na baya, na tsafin da ya tilasta su su shirya don su yi nasara a kan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Suka bayyana masa cewa, sakamakon da Allah zai yi musu a kan imaninsu ya fi tagomashi a kan abin da shi ya yi musu alƙawarin zai ba su idan sun yi nasarar murƙushe Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Hakanan azabar Allah ta fi ɗorewa da dawwama a kan wadda yake kurarin zai yi musu don sun yi imani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirai ‘yan wuta za su dawwama a cikinta ba za su yi rai ba kuma ba za su mutu ba saboda tsananin azabarta.

2. Ayyukan ƙwarai su ne sababin shiga Aljanna a ranar alƙiyama.

3. ‘Yan Aljanna mataki-mataki ne, wasu suna saman wasu gwargwadon ayyukan kowa a nan duniya.

Suratu Ɗa Ha (74-76)

إِنَّهُۥ مَن يَأۡتِ رَبَّهُۥ مُجۡرِمٗا فَإِنَّ لَهُۥ جَهَنَّمَ لَا يَمُوتُ فِيهَا وَلَا يَحۡيَىٰ ٧٤ وَمَن يَأۡتِهِۦ مُؤۡمِنٗا قَدۡ عَمِلَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلدَّرَجَٰتُ ٱلۡعُلَىٰ ٧٥ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَذَٰلِكَ جَزَآءُ مَن تَزَكَّىٰ ٧٦

74. Lalle duk wanda ya zo wa Ubangijinsa yana mai babban laifi to lalle yana da (sakamakon) Jahannama, ba zai mutu a cikinta ba, ba kuma zai rayu ba (rayuwa mai daɗi)

75. Wanda kuwa ya zo masa yana mumini ya zamana ya yi aiki na gari, to waɗannan suna da (sakamakon samun) darajoji maɗaukaka.

76. (Watau) gidajen Aljanna na dawwama waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, masu dawwama ne a cikinsu. Wannan kuwa shi ne sakamakon wanda ya tsarkaka (daga saɓo).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙarin bayani ne a kan matsayar da matsafa suka ɗauka ta yin imani da Allah da watsi da duk wani aiki na kafirci da sihiri da suke a kai. Allah ya bayyana cewa, lalle yadda lamarin yake dai shi ne, duk wanda ya je wa Ubangijinsa ranar alƙiyama alhali yana kafiri, to tabbas wannan wutar Jahannama ce makomarsa, zai shige ta ya yi ta zama har abada, ba zai mutu ba balle ya huta daga azaba, ba kuma zai yi wata kyakkyawar rayuwa ba.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Amma 'yan wuta waɗanda su ne 'yan wuta, to waɗannan ba za su mutu ba a cikinta, ba kuma za su rayu ba..." [Muslim #185].

Sannan kuma Allah ya bayyana cewa wanda ya gamu da shi yana mumini ya kuma yi kyawawan ayyuka, to masu irin waɗannan kyawawan halaye suna da sakamakon waɗansu darajoji maɗaukaka.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle 'yan Aljanna suna hango ma'abota wasu ɗakuna a samansu kamar yadda kuke hango tauraro mai haske mai shuɗewa a sararin samaniya na gabas ko na yamma, saboda fifikon da ke tsakaninsu." Sai sahabbai suka ce: "Ya Manzon Allah, waɗannan masaukai ne na annabawa, ban da su babu mai kai wa gare su?" Sai ya ce: "Ba haka ne ba, na rantse da wanda raina yake hannunsa, waɗannan wasu mutane ne da suka yi imani da Allah suka kuma gaskata manzanni." [Bukhari #6555 da Muslim #2831].

Allah ya bayyana cewa wannan shi ne sakamakon duk wanda ya tsarkaka daga kafirci da saɓon Allah, ko dai saboda bai taɓa aikata su ba, ko kuma ya aikata su amma ya tuba ya tsarkake kansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawa ba sa aikata wani abu da ya shafi makomar al'ummarsu sai sun jira wahayi daga Allah. Annabi Musa bai fita da mutanensa daga Masar ba don yin hijira har sai da wahayi daga Allah ya zo masa yana umartar sa da yin haka tare da sanar da shi abin da zai yi a hanyarsu ta fita.

2. Duk sanda zuciya ta cika da imani da Allah da yarda da alƙawarinsa, to babu abin da zai tsorata ta ko ya sanya ta ta karaya.

3. Al’adar Allah ce tare da bayinsa muminai cewa yana yi musu sakayya game da zaluncin azzalumai a gare su, ya saukar wa da waɗannan azzaluman azabarsa don ya shigar da farin ciki a zukatan bayinsa muminai waɗanda ake zalunta.

4. Shugaba azzalumi wanda ya kauce wa hanyar Allah koyaushe yakan zamanto annoba kuma alaƙaƙai ga kansa da kuma al’ummarsa, domin ba zai taɓa ɗora su a kan kyakkyawar turbar rayuwa ba, kuma koyaushe zai yi ta jan su ne a cikin ɓata.

5. Ni’imomin Allah ga bayinsa suna buƙatar godiya koyaushe daga gare su, domin ya ci gaba da tsare musu su, ya kuma haɓaka musu su. Hakanan butulce wa ni’imomin Allah yana haifar da saukar fushinsa ga bayinsa ya kai su ga hallaka duniya da lahira.

6. Allah mai yawan gafara ne ga bayinsa masu tuba su bar shirka da kafirci da aikin saɓo, masu kyawawan ayyuka, masu dagewa a kan haka har lokacin mutuwarsu.

Suratu Ɗa Ha (77-82)

وَلَقَدۡ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنۡ أَسۡرِ بِعِبَادِي فَٱضۡرِبۡ لَهُمۡ طَرِيقٗا فِي ٱلۡبَحۡرِ يَبَسٗا لَّا تَخَٰفُ دَرَكٗا وَلَا تَخۡشَىٰ ٧٧ فَأَتۡبَعَهُمۡ فِرۡعَوۡنُ بِجُنُودِهِۦ
فَغَشِيَهُم مِّنَ ٱلۡيَمِّ مَا غَشِيَهُمۡ ٧٨ وَأَضَلَّ فِرۡعَوۡنُ قَوۡمَهُۥ وَمَا هَدَىٰ ٧٩ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ قَدۡ أَنجَيۡنَٰكُم مِّنۡ عَدُوِّكُمۡ وَوَٰعَدۡنَٰكُمۡ جَانِبَ
ٱلطُّورِ ٱلۡأَيۡمَنَ وَنَزَّلۡنَا عَلَيۡكُمُ ٱلۡمَنَّ وَٱلسَّلۡوَىٰ ٨٠ كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقۡنَٰكُمۡ وَلَا تَطۡغَوۡاْ فِيهِ فَيَحِلَّ عَلَيۡكُمۡ غَضَبِي وَمَن يَحۡلِلۡ عَلَيۡهِ
غَضَبِي فَقَدۡ هَوَىٰ ٨١ وَإِنِّي لَغَفَّارٞ لِّمَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا ثُمَّ ٱهۡتَدَىٰ ٨٢

77. Haƙiƙa kuma Mun yi wa Musa wahayi cewa: “Ka tafi da bayina cikin dare sannan ka keta musu hanya ƙeƙasasshiya a cikin ƙogi, ba za ka ji tsoron riskar (Fir’auna da jama’arsa) ba, kuma ba za ka ji tsoron (nutsewa) ba.”

78. Sai Fir’auna ya bi su shi da rundunarsa sai abin da ya haɗe su na ruwan ƙogi ya haɗiye su (suka hallaka kakaf)!

79. Fir’auna kuma ya ɓatar da mutanensa bai kuma shiryar (da su) ba.

80. Ya ku Banu-Isra’ila, haƙiƙa Mun tserar da ku daga maƙiyinku, (watau Fir’auna) Muka kuma yi muku alƙawarin (ganawa) a ɓarin dama na dutsen Ɗuri, Muka kuma saukar muku da darɓa da kuma (gasassun tsuntsayen) salwa.

81. Ku ci daga daɗaɗan abin da Muka arzuta ku da shi (na halal), kada kuwa ku ƙetare shi (zuwa haramun), sai fushina ya faɗa muku; wanda kuwa fushina ya faɗa masa, to haƙiƙa ya hallaka.

82. Lalle Ni kuma Mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba kuma ya yi aiki na gari sannan ya (tabbata bisa) shiriya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana umarnin da ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa ya tattara mutanensa Banu Isra’ila waɗanda suka yi imani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fita da su daga ƙasar Masar cikin dare ba tare da wani ya gan su ba, ya kuma umarce shi da ya keta musu hanya busasshiya ta cikin ƙogi bayan ya doke shi da sandarsa,

wadda za su bi su ratsa ba tare da sun ji tsoron Fir’auna da rundunarsa su cim masu ba, ko su ji tsoron nutsewa a cikin ruwa.
Sai Annabi Musa ya aikata abin da Allah ya umarce shi da yi. Bayan sun fita cikin dare sai Fir’auna da rundunarsa suka bi su a baya. Annabi Musa ya doki kogi da sandarsa sai ruwansa ya dare gida biyu, suka ga hanya ɗoɗar suka bi. Shi ma Fir’auna da rundunarsa da suka iso ba da wata-wata ba sai kawai suka bi wannan hanyar. Nan-take kuwa kogin ya haɗe da su gaba ɗaya, suka hallaka, Annabi Musa kuwa da mutanensa suka tsira.
Sai Allah ya tabbatar da cewa Fir’auna fa ya ɓatar da mutanensa ne kawai a lamarin addininsu da na rayuwarsu, bai taɓa ɗora su a kan hanyar shiriya ba tun da suke tare da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da zayyana wa Banu Isra’ila irin ni’imomin da ya yi musu da cewa, shi ne ya tserar da su daga babban maƙiyinsu Fir’auna da rundunarsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da Manzon Allah (ﷺ) ya iso Madina ya samu Yahudawa suna azumin Ashura sai ya tambaye su, sai suka ce: “Wannan ita ce ranar da Allah ya ba wa Musa nasara a kan Fir’auna a cikinta.” Sai ya ce: “Mun fi su cancantar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), don haka ku yi azumi.” [Bukhari #4737 da Muslim #1130].

Allah kuma ya yi musu alƙawarin ganawa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a gefen dama na dutsen Ɗuri domin yin magana da shi da ba shi littafin Attaura mai ƙunshe da haske da shiriya da bayanin shari’arsu.
Bayan haka kuma ya saukar musu da darɓa da kuma gasassun tsuntsayen salwa masu kama da fakara masu daɗin nama. Allah ya umarce su da su ci daɗaɗan abubuwa na halal da ya arzuta su da su, kada kuma su kuskura su tsallake abin da ya halatta musu zuwa ga abubuwan da ya haramta musu, ko su riƙa yin almubazzaranci da abin da ya arzuta su da shi na halal ko su yi amfani da shi wajen saɓa masa ko su ce za su hana haƙƙoƙi na wajibi da ke kansu. Idan sun yi haka to fushin Allah zai tabbata a kansu; duk kuwa wanda fushin Allah ya tabbata a kansa, to babu shakka ya taɓe duniya da lahira ba zai taɓa rabauta ba har abada.
Sai kuma ya tabbatar da cewa shi mai yawan gafara ne ga duk wanda ya tuba tuba na gaskiya, ya kuma yi aiki na ƙwarai, sannan ya tsaya kyam a kan gaskiya har mutuwarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk da cewa ba a son yawan gaggawa cikin al’amura, to amma idan ta kasance game da neman yardar Allah ne to abu ne mai kyau.

2. Fushi a kan an keta dokar Allah abu ne mai kyau abin yabo.

3. Yaudarar mutane ta hanyar ƙawata musu ƙarya da canza haƙiƙanin abubuwa daga yadda suke wata hanya ce ta ɓatattun mutane.

4. Tabbatar wa da Allah siffar fushi yadda ya dace da Zatinsa maɗaukaki.

5. Tabbatar wa da Allah siffar magana, domin siffa ce ta kamala, don haka Allah ya kafa wa Banu Isra’ila hujja da cewa ba sa ganin ɗan maraƙin Samiri ba ya iya magana da su? Watau wannan kaɗai ya isa ya sanya su su fahimci cewa ba abin bauta ne na gaskiya ba don yana da tawaya.

Suratu Ɗa Ha (83-89)

*وَمَآ أَعۡجَلَكَ عَن قَوۡمِكَ يَٰمُوسَىٰ ٨٣ قَالَ هُمۡ أُوْلَآءِ عَلَىٰٓ أَثَرِي وَعَجِلۡتُ إِلَيۡكَ رَبِّ لِتَرۡضَىٰ ٨٤ قَالَ فَإِنَّا قَدۡ فَتَنَّا قَوۡمَكَ مِنۢ بَعۡدِكَ وَأَضَلَّهُمُ ٱلسَّامِرِيُّ ٨٥ فَرَجَعَ مُوسَىٰٓ إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ غَضۡبَٰنَ أَسِفٗاۚ قَالَ يَٰقَوۡمِ أَلَمۡ يَعِدۡكُمۡ رَبُّكُمۡ وَعۡدًا حَسَنًاۚ أَفَطَالَ عَلَيۡكُمُ ٱلۡعَهۡدُ أَمۡ أَرَدتُّمۡ أَن يَحِلَّ عَلَيۡكُمۡ غَضَبٞ مِّن رَّبِّكُمۡ فَأَخۡلَفۡتُم مَّوۡعِدِي ٨٦ قَالُواْ مَآ أَخۡلَفۡنَا مَوۡعِدَكَ بِمَلۡكِنَا وَلَٰكِنَّا حُمِّلۡنَآ أَوۡزَارٗا مِّن زِينَةِ ٱلۡقَوۡمِ فَقَذَفۡنَٰهَا فَكَذَٰلِكَ أَلۡقَى ٱلسَّامِرِيُّ ٨٧ فَأَخۡرَجَ لَهُمۡ عِجۡلٗا جَسَدٗا لَّهُۥ خُوَارٞ فَقَالُواْ هَٰذَآ إِلَٰهُكُمۡ وَإِلَٰهُ مُوسَىٰ فَنَسِيَ ٨٨ أَفَلَا يَرَوۡنَ أَلَّا يَرۡجِعُ إِلَيۡهِمۡ قَوۡلٗا وَلَا يَمۡلِكُ لَهُمۡ ضَرّٗا وَلَا نَفۡعٗا ٨٩

83. Kuma me ya sa ka gaggawar barin mutanenka, ya Musa?

84. (Musa) ya ce: “Su waɗannan (mutane nawa) ai za su biyo bayana ne (ba da jimawa ba), na kuwa yi gaggawa ne zuwa gare Ka ya Ubangijina don neman yardarka.”

85. (Allah) ya ce: “To lalle Mun jarrabi mutanenka a bayanka, Samiri kuma ya ɓatar da su.”

86. Sai Musa ya komo zuwa ga mutanensa cike da fushi da baƙin ciki. Ya ce: “Ya ku mutanena, yanzu Ubangijinku bai yi muku kyakkyawan alƙawari ba? Ko kuwa lokacin alƙawarin ne ya yi muku tsawo? Ko kuwa kuna so ne fushin Ubangijinku ya saukar muku, shi ne sai kuka saɓa alƙawarin (da muka yi na ku tabbata bisa imani)?”

87. Suka ce: “Ba mu saɓa alƙawarinka da zaɓin kanmu ba, sai dai mu an ɗora mana kayayyakin nauyi ne na ababan adon mutane (Ƙibɗawa), sai muka jefa su (a cikin wuta), sannan Samiri ya jefa (nasa) kamar yadda (muka yi).”

88. To sai ya fitar musu da ɗan maraƙi jika-jika mai kuka, sai suka ce: “Wannan ubangijinku ne kuma ubangijin Musa, amma sai ya manta (da yana nan).”

89. Yanzu ba sa gani cewa (maraƙin) ba ya mayar musu da magana, kuma ba ya mallakar wata cuta ko amfani gare su?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da ya faru bayan ya hallaka Fir’auna da rundunarsa ya kuma tserar da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da jama’arsa, da cewa, ya yi wa Musa alƙawarin ganawa da shi bayan kwana arba’in don ya ba shi littafin Attaura da zai karantar da mutanensa. Lokacin da wa’adin ganawarsu ya yi sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi gaggawa ya je wajen ganawar ba tare da ya tafi tare da wani daga cikin manyan Banu Isra’ila ba, domin yana cike da shauƙi da ɗokin wannan haɗuwa tasa da Ubangijinsa, sai Allah ya tambaye shi cewa, me ya sa ya yi gaggawar barin mutanensa a baya bai zo tare da su ba? Sai Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya faɗi uzurinsa da cewa ya baro su ne a baya domin ba da jimawa ba su ma za su biyo shi; ya kuma yi gaggawar tahowa ne saboda yana cike da ɗokin ganin ya sami yardar Ubangijinsa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da shi cewa, bayan barinsa ya jarrabi mutanensa sun auka ga bautar ɗan maraƙi, kuma ba kowa ne ya jefa su a cikin wannan hallaka ba sai Samiri shi ne ya ɓatar da su.Da jin haka sai Musa ya juya cike da fushi da baƙin ciki a kan abin da ya faru ga mutanensa, ya koma ya same su ya ƙalubalance su da cewa, yanzu sun manta ne Allah ya yi musu kyakkyawan alƙawari na cewa zai saukar musu da littafin Attaura ya kuma shigar da su gidan Aljanna idan sun mutu? Shin lokacin ne ya yi musu tsawo har suka manta da abin da ya ɗora su a kai, ko kuma dai kawai sun yi haka ne da gangan

domin fushin Allah ya saukar musu, azabarsa ta tabbata a kansu, shi ya sa suka saba alkawarinsa na tabbata a kan ɗa'a har ya dawo?
Sai suka amsa wa Musa da cewa, ba da raɗin kansu ne suka saba alkawarinsa ba, su dai an ɗora musu kayan ado na mutanen Fir'auna sun fito da shi, sai suka ga ba za su iya amfani da su ba, sai suka yi rami suka jefa su, shi ma kuma Samiri sai ya kawo wata ƙasa da ya ɗamƙa daga ƙarƙashin kofaton dokin Jibril (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya jefa a cikin ramin nan. To daga waɗannan kayan ado ne Samiri ya fitar musu da wannan ɗan maraki jika-jika marar rai amma yana kuka irin na 'yan maruƙa. Ganin haka sai wasu fitinannu daga cikinsu suka ce: "Wannan shi ne abin bautarku kuma abin bautar Musa, amma ya manta shi a nan ya tafi neman sa cikin duwatsu."
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu martani a kan wannan wautar tasu da cewa, shin ba sa ganin wannan ɗan maraki ba ya iya magana da su, ba kuma sa iya tattaunawa da shi, sannan ba ya mallakar wata cuta ko wani amfani gare su?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tabbata cewa a cikin mutanensa lalle Haruna bai bauta wa ɗan maraki ba shi ya sa ya ware shi ya yi masa magana, domin ba zai yiwu annabin Allah ya bauta wa wani ba Allah ba.

2. Annabi Haruna ya kirawo Annabi Musa da ɗan ummata duk da kasancewarsu shaƙiƙai ne uwa ɗaya uba ɗaya; ya yi hakan ne don tayar masa da tausayinsa gare shi, kamar yadda uwa take tausayin ɗanta.

3. Barin gemu sunna ce ta annabawan Allah.

4. Annabi Haruna ya zabi zama cikin mutanensa bai ƙyale su ya bi ɗan'uwansa Musa ba, domin idan ya yi haka zai bar su babu shugabanci, wanda hakan na iya haifar da rarrabuwa a tsakaninsu wadda za ta iya kaiwa ga salwantar rayuka da dukiya da rushewar tsarin zamantakewa. Amma abin da suka runguma na bautar ɗan maraki ana iya shawo kansa yayin da Annabi Musa ya dawo ya tsawatar musu, musamman ma sun nuna suna jiran dawowarsa ne don su ji hukuncin da zai zartar. To amma matsayar da Annabi Musa ya ɗauka ita ce mafi dacewa a nan, domin kare tushen aƙida yana gaba da kare tsarin haɗin kan zamantakewa.

5. Wajabcin korar maɓarnaci daga cikin al'umma, musamman wanda ɓarnarsa ta shafi addini, kamar mai yaɗa wata muguwar bidi'a a cikin Musulmi.

6. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ƙona ɗan marakin nan ya sheƙe tokarsa a ruwa don ya tabbatar musu da cewa shi ba Allah ne ba, domin da shi ne Allah da gaske, to da ya kare kansa ya hana Musa ya salwantar da shi. Kuma son bautar ɗan maraki ya riga ya shiga zukatan Banu Isra'ila, don haka Musa ya gama da wannan ɗan maraki gaba ɗaya a gabansu ko sun yi niyyar dawo da shi ba za su iya ba, domin da haka ne son sa zai fita daga zukatansu gaba ɗaya.

Suratu Ɗa Ha (90-98)
وَلَقَدۡ قَالَ لَهُمۡ هَٰرُونُ مِن قَبۡلُ يَٰقَوۡمِ إِنَّمَا فُتِنتُم بِهِۦۖ وَإِنَّ رَبَّكُمُ ٱلرَّحۡمَٰنُ فَٱتَّبِعُونِي وَأَطِيعُوٓاْ أَمۡرِي ٩٠ قَالُواْ لَن نَّبۡرَحَ عَلَيۡهِ عَٰكِفِينَ حَتَّىٰ
يَرۡجِعَ إِلَيۡنَا مُوسَىٰ ٩١ قَالَ يَٰهَٰرُونُ مَا مَنَعَكَ إِذۡ رَأَيۡتَهُمۡ ضَلُّوٓاْ ٩٢ أَلَّا تَتَّبِعَنِۖ أَفَعَصَيۡتَ أَمۡرِي ٩٣ قَالَ يَبۡنَؤُمَّ لَا تَأۡخُذۡ بِلِحۡيَتِي وَلَا بِرَأۡسِيٓۖ إِنِّي
خَشِيتُ أَن تَقُولَ فَرَّقۡتَ بَيۡنَ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ وَلَمۡ تَرۡقُبۡ قَوۡلِي ٩٤ قَالَ فَمَا خَطۡبُكَ يَٰسَٰمِرِيُّ ٩٥ قَالَ بَصُرۡتُ بِمَا لَمۡ يَبۡصُرُواْ بِهِۦ فَقَبَضۡتُ

قَبۡضَةٗ مِّنۡ أَثَرِ ٱلرَّسُولِ فَنَبَذۡتُهَا وَكَذَٰلِكَ سَوَّلَتۡ لِي نَفۡسِي ٩٦ قَالَ فَٱذۡهَبۡ فَإِنَّ لَكَ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ أَن تَقُولَ لَا مِسَاسَۖ وَإِنَّ لَكَ مَوۡعِدٗا لَّن تُخۡلَفَهُۥۖ وَٱنظُرۡ إِلَىٰٓ إِلَٰهِكَ ٱلَّذِي ظَلۡتَ عَلَيۡهِ عَاكِفٗاۖ لَّنُحَرِّقَنَّهُۥ ثُمَّ لَنَنسِفَنَّهُۥ فِي ٱلۡيَمِّ نَسۡفٗا ٩٧ إِنَّمَآ إِلَٰهُكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِي لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ وَسِعَ كُلَّ شَيۡءٍ عِلۡمَا ٩٨

90. Alhali kuwa haƙiƙa Haruna ya faɗa musu tun da wuri cewa: “Ya ku mutanena, an jarrabe ku da shi ne kawai, kuma lalle Ubangijinku (na gaskiya) Shi ne Arrahamanu, sai ku bi ni kuma ku bi umarnina.”

91. Suka ce: “Ba za mu gushe muna duƙufa wajen bauta masa ba har sai Musa ya dawo mana.”

92. (Musa) ya ce: “Ya Haruna, me ya hana ka lokacin da ka gan su sun ɓace?

93. “Ka bi ni (don ka sanar da ni)? Ko kuwa ka saɓa umarnina ne?”

94. (Haruna) ya ce: “Ya ɗan’ummata, kada ka kama mini gemuna, da kuma (gashin) kaina; lalle ni na ji tsoron ka ce (da ni): ‘Ka rarraba kan Banu-Isra’ila, ba ka kuma kiyaye maganata ba.’”

95. (Musa) ya ce: “Mene ne lamarinka, ya Samiri?”

96. Ya ce: “Na ga abin da ba su gani ba ne, sai na ɗebi danƙi daga gurbin (ƙasar) sawun (goɗiyar) Manzon (wato Jibrilu) sannan na watsa ta (a kan ɗan maraƙin). Kamar haka kuwa raina ya ƙawata mini.”

97. (Annabi Musa) ya ce: “To sai ka tafi, amma ka tabbatar cewa (sakamakonka) a rayuwar (da za ka yi) shi ne ka riƙa cewa ‘*la misasa*’, (wato ba za ka taɓu ba kuma ba za ka taɓa kowa ba); kuma lalle kana da ƙayyadajjen lokaci wanda ba za a saɓa maka ba; kuma ka dubi ubangijin naka wanda ka duƙufa a kansa kana bauta; lalle za mu ƙona shi sannan tabbas za mu sheƙar da shi cikin kogi.”

98. Abin bautarku kawai shi ne Allah wanda babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi. Ya yalwaci komai da iliminsa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, tun can farko ma Annabi Haruna sai da ya yi wa Banu Isra’ila wa’azi lokacin da ya gan su sun koma bautar ɗan maraƙi, ya tabbatar musu da cewa wannan jarraba ce Allah yake nufin yi musu don gwada ƙarfin imaninsu da shi, ya kuma ware mumini na gaskiya daga cikinsu da kafiri, ya kuma shaida musu cewa Ubangijinsu na gaskiya shi ne Allah mai rahama ba wani wanda ba zai iya mallaka musu amfani ko cuta ba ballantana ma har ya ji ƙan su. Don haka ya kirawo su a kan su dawo su bi shi su bauta wa Allah shi kaɗai su bar bautar ɗan maraƙi. To amma sai fitinannun cikinsu suka mayar masa da amsa cewa su fa ba za su taɓa barin bautar wannan ɗan maraƙi ba har sai Musa ya dawo ya yi musu bayanin cewa ba a kan gaskiya suke ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin yadda Annabi Musa ya nuna wa ɗan’uwansa Haruna ɓacin ransa game da wannan abu da ya faru bayan tafiyarsa, ya zarge shi da cewa, me ya hana shi lokacin da ya ga mutanensa sun saki hanya sun kama bautar ɗan maraƙi ya bi shi can inda yake tare da sauran Banu Isra’ila waɗanda ba su yarda da bautarsa ba don ya sanar da shi? Ko kuma dai ya saɓa wa umarninsa ne lokacin da ya bar shi tare da su don kula da su; ya kuma umarce shi da yin gyara a tsakaninsu kada ya yarda ya bi hanyar maɓarnata?!
Sai Musa cikin fushi da ɓacin rai ya kama gemun ɗan’uwansa Haruna da gashin kansa yana ja, sai Haruna ya ce masa, ya daina ja masa gemunsa da gashin kansa; ya bayyana masa hanzarinsa na rashin barinsa ya bi shi da cewa, idan ya tafi ya bar su yana jin tsoron kada Annabi Musa ya zarge shi da cewa ya raba masa

kan al'ummarsa kuma bai yi aiki da wasiyyar da ya bar masa ba ta cewa ya yi gyara a cikinsu. Don haka ya zaɓi ya yi haƙuri ya ci gaba da zama tare da su har sanda Musa ya dawo, sai ya ga yadda za a shawo kan matsalar.
Bayan Annabi Musa ya ji uzurin ɗan'uwansa Haruna kuma ya gamsu, sai ya juya wajen Samiri ya tambaye shi shi kuma mene ne lamarinsa? Me ya sa shi ya aikata abin da ya aikata ɗin nan?
Sai Samiri ya faɗa wa Annabi Musa cewa shi ya ga abin da sauran Banu Isra'ila ba su gani ba, domin ya ga Mala'ika Jibrila a kan dokinsa lokacin da ya zo hallaka Fir'auna da jama'arsa, sai ya damƙi ƙasar ƙafafun dokinsa ya watsa ta cikin narkakken kayan ado bayan ya yi masa ginin surar ɗan maraƙi, sai ya zama wani jika-jikan ɗan maraƙi yana gunji kamar mai rai. Samiri ya ƙara da cewa haka ransa ya ƙawata masa ya aikata kuma ya bi son ransa.
Da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ji bayanin Samiri da yadda ya shirya hallakar da Banu Isra'ila, yana kuma faɗa cikin gadara da cika baki, sai Annabi Musa ya yi tir da aikinsa kuma ya bayyana masa mummunan sakamakon da yake jiran sa duniya da lahira. A nan duniya ya ce masa ya tafi ya ɓace masa da gani, kuma matsawar dai yana a raye to ba zai iya gauraya da mutane ba, domin duk sanda ya ga wani ya nufo shi zai ce masa: "*La misasa*" watau kada a taɓa jikinsa, shi ma kuma ba zai iya taɓa jikin kowa ba. Haka zai yi ta rayuwa cikin wannan azabar har mutuwarsa. A lahira kuwa yana da wani ƙayyadajjen lokaci da yake jiran sa wanda ba zai iya kauce masa ba, a inda Allah zai yi masa hisabi a kan mummunan aikinsa ya gamu da matsananciyar azaba ta har abada.
Sai kuma Annabi Musa ya juya wajen ɗan maraƙin da Samiri yake bauta wa don ya tabbatar masa shi da waɗanda suka hallaka tare da shi cewa wannan ba abin bauta ba ne, kuma zai hura wuta ya ƙona shi, bayan ya zama toka kuma zai sheƙar da shi a cikin kogi ta yadda ba wanda zai sake ganin sa har abada. Annabi Musa ya yi haka ne don ya tabbatar da cewa ba abin bauta ba ne; da kuwa abin bauta ne na gaskiya, to da babu mai iya yi masa haka.
Sai kuma Annabi Musa ya dawo kan Banu Isra'ila ya ƙara tunatar da su kalmar Tauhidi da bautar Allah shi kaɗai wanda ya siffantu da siffofi na kamala, wanda iliminsa ya kewaye komai, don haka shi kaɗai ne abin bauta da gaskiya, babu wani abin bauta bayan shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani littafi ne da yake ɗauke da faɗakarwa a kan sunayen Allah da siffofinsa da ayyukansa cikakku, yana kuma ɗauke da fayyatattun bayanai a kan hukunce-hukunce waɗanda suka ƙunshi umarni da hani, waɗanda kuma duk wani mai cikakken hankali zai ba da shaida a kan nagartarsu da dacewarsu ga rayuwar ɗan'adam a koyaushe. Don haka ya zama wajibi ga mutane su yi imani da Alƙur'ani su miƙa wuya su sallama wa hukunce-hukuncensa.

2. Alƙur'ani wa'azi ne da faɗakarwa ga al'ummu da ɗaiɗaikun mutane, don haka labarun cikinsa ba kawai labaru ne na ɗebe kewar masu karatu ba; manufarsu tunatarwa ne da jan hankali da bayar da darussa daban-daban na rayuwa ga mutane.

3. Rashin tsawon kwanakin duniya komai yawansu idan an kwatanta su da kwanakin lahira waɗanda ba sa yankewa, ba su da ƙarshe.

4. Tabbatar da busar ƙaho ta biyu wadda Mala'ika Israfilu zai yi don tashin matattu daga ƙaburburansu, domin yi musu hisabi a gaban Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da yi wa kowa sakamako gwargwadon ayyukansa a nan duniya.

Suratu Ɗa Ha (99-104)

كَذَٰلِكَ نَقُصُّ عَلَيْكَ مِنْ أَنۢبَآءِ مَا قَدْ سَبَقَ ۚ وَقَدْ ءَاتَيْنَٰكَ مِن لَّدُنَّا ذِكْرًا ﴿٩٩﴾ مَّنْ أَعْرَضَ عَنْهُ فَإِنَّهُۥ يَحْمِلُ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ وِزْرًا ﴿١٠٠﴾ خَٰلِدِينَ فِيهِ ۖ وَسَآءَ لَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ حِمْلًا ﴿١٠١﴾ يَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ ۚ وَنَحْشُرُ ٱلْمُجْرِمِينَ يَوْمَئِذٍ زُرْقًا ﴿١٠٢﴾ يَتَخَٰفَتُونَ بَيْنَهُمْ إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا عَشْرًا ﴿١٠٣﴾ نَّحْنُ أَعْلَمُ بِمَا يَقُولُونَ إِذْ يَقُولُ أَمْثَلُهُمْ طَرِيقَةً إِن لَّبِثْتُمْ إِلَّا يَوْمًا ﴿١٠٤﴾

99. Kamar haka ne Muke ba ka labari daga labaran abubuwan da suka riga suka wuce. Haƙiƙa kuwa Mun ba ka Alƙur'ani daga wajenmu.

100. Duk wanda ya bijire masa to lalle zai ɗauki nauyin zunubi a ranar alƙiyama.

101. (Suna) madawwama a cikinsa (zunubin); kayan (zunubi) kuwa ya munana a gare su ranar alƙiyama.

102. (Ita ce) ranar da za a busa ƙaho. Kuma Mu tayar da kafirai a wannan ranar idanuwansu jawur.

103. Suna raɗa a tsakaninsu (suna cewa): "Ba ku zauna (a ƙaburburanku) ba face (kwana) goma."

104. Mu Muka fi sanin abin da suke faɗi lokacin da wanda ya fi tunani daga cikinsu yake cewa: "Ba ku zauna ba face rana guda."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) babbar manufar da take ƙunshe a cikin labarurrukan Alƙur'ani, da cewa, kamar yadda ya ba shi labarin Annabi Musa da Fir'auna da mutanensa, to hakanan yake ba shi labaran annabawan da suka gabace shi tare da al'ummunsu, domin su zama abin ɗebe kewa a gare shi, kuma Allah yana tabbatar masa da cewa ya saukar masa da Alƙur'ani ne don masu wa'azantuwa su wa'azantu da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi duk wanda zai bijire wa Alƙur'ani ya ƙi imani da shi ko ya ƙi aiki da shi cewa ranar alƙiyama zai zo yana ɗauke da nauyin zunubi mai girma a kansa, sai ya cancanci matsananciyar azaba wadda ita ce wutar Jahannama, zai kuma dawwama har abada a cikinta. Allah kuma ya yi tir da wannan kayan zunubi da zai ɗauka a ranar alƙiyama.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta wannan rana ta alƙiyama da cewa rana ce da za a yi busar ƙaho ta biyu inda Allah zai tayar da kafirai a firgice idanuwansu jawur saboda tsananin tsoro da fargaba, ba abin da suke iya yi sai raɗa a tsakaninsu, suna faɗa wa junansu cewa, ai kwana goma kacal suka yi a ƙaburburansu; sun ma kasa tuna kwanakin da suka yi a duniya balle su iya tuna tsawon zamansu na barzahu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi ne ya fi kowa sanin maganganun da suke tattaunawa da junansu cikin raɗa. wanda ya fi kaifin hankali a cikinsu ma shi yake faɗa cewa, kwana ɗaya ne kacal suka yi a barzahu bai ma kai goma ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ruɗanin da mushirikai suka shiga game da ranar alƙiyama dangane da waɗannan manya-manyan duwatsu a doron ƙasa; suna ganin idan har Allah zai tashi alƙiyama yayin da duniya ta ƙare, yaya za a yi da waɗannan duwatsun? Sai Allah ya saukar wa da Annabi (ﷺ) amsar tambayarsu don ya kawar musu da wannan ruɗani da ke tare da su.

2. Ranar alƙiyama rana ce da kowa da komai zai rusuna gaban Allah, babu bambanci tsakanin masu mulki da talakawansu, da masu wadata da matalauta, da iyayen gida da bayinsu, babba da yaro, namiji ko

mace, tsoho da matashi. Duk za su kasance a durƙushe a kan gwiwoyinsu a gaban mahaliccinsu, babu mai iya magana sai wanda Allah ya yi masa izini da yin magana; kowa yana sauraron hukuncin da Ubangijinsa zai zartar a kansa. Sai dai kuma rahamar Allah marar iyaka za ta baibaye halittunsa a wannan lokaci, don haka ne ma ya kirawo kansa da 'Mai rahama'.

3. Ceto a ranar alƙiyama gaskiya ne. Sai dai babu mai yin ceto sai da sharuɗɗa guda biyu:
Na farko, Allah ya ba wa wanda zai yi ceto izinin yin ceto.
Na biyu, Allah ya yarda da ceton wanda za a ceta. Don haka ceto ba zai taɓa amfanar kafirai ba, domin Allah bai yarda da kafirci ba.

4. Mummunan sakamakon zalunci. Don haka duk wanda ya je wa Ubangijinsa yana ɗauke da zalunci, to ya yi babbar hasara ya taɓe.

5. Aikin ƙwarai ba ya zama karɓaɓɓe a wurin Allah sai ya haɗu da imanin mai aikin.

6. Bayanin cikar adalcin Allah ranar alƙiyama.

Suratu Ɗa Ha (105-112)
وَيَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلْجِبَالِ فَقُلْ يَنسِفُهَا رَبِّى نَسْفًا ﴿١٠٥﴾ فَيَذَرُهَا قَاعًا صَفْصَفًا ﴿١٠٦﴾ لَّا تَرَىٰ فِيهَا عِوَجًا وَلَآ أَمْتًا ﴿١٠٧﴾ يَوْمَئِذٍ يَتَّبِعُونَ ٱلدَّاعِىَ لَا عِوَجَ لَهُۥ ۖ وَخَشَعَتِ ٱلْأَصْوَاتُ لِلرَّحْمَٰنِ فَلَا تَسْمَعُ إِلَّا هَمْسًا ﴿١٠٨﴾ يَوْمَئِذٍ لَّا تَنفَعُ ٱلشَّفَـٰعَةُ إِلَّا مَنْ أَذِنَ لَهُ ٱلرَّحْمَـٰنُ وَرَضِىَ لَهُۥ قَوْلًا ﴿١٠٩﴾ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ وَلَا يُحِيطُونَ بِهِۦ عِلْمًا ﴿١١٠﴾ ۞ وَعَنَتِ ٱلْوُجُوهُ لِلْحَىِّ ٱلْقَيُّومِ ۖ وَقَدْ خَابَ مَنْ حَمَلَ ظُلْمًا ﴿١١١﴾ وَمَن يَعْمَلْ مِنَ ٱلصَّـٰلِحَـٰتِ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَا يَخَافُ ظُلْمًا وَلَا هَضْمًا ﴿١١٢﴾

105. Suna kuma tambayar ka game da duwatsu, to ka ce (da su): "Ubangijina zai niƙe su tilis.

106. "Sannan Ya bar ta (wato ƙasar) fili fetal.

107. "Ba za ka ga wani kwari ko tudu a kanta ba."

108. A wannan rana ne za su bi mai kira (zuwa matattara), ba mai bauɗe masa; kuma (duk) muryoyi su yi ƙasa-ƙasa saboda (girman Allah) Mai rahama, sannan ba za ka ji (komai) ba sai raɗa.

109. A wannan ranar ceto ba ya amfani sai ga wanda (Allah) Mai rahama Ya yi wa izini, kuma Ya yarda da maganarsa.

110. (Allah) Yana sane da abin da yake gaba gare su (na ranar alƙiyama) da kuma abin da yake bayansu (na ayyukan da suka yi a duniya), su kuwa ba za su kewaye da saninsa ba.

111. Kuma dukkanin fuskoki suka ƙasƙanta ga (Allah) Rayayye, Tsayayye (da Zatinsa). Haƙiƙa kuma duk wanda ya yo dakon zalunci ya taɓe.

112. Duk kuma wanda yake yin aiki na gari alhali kuwa shi mumini ne, to ba zai ji tsoron zalunci ba ko kuma ƙwauro.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta yadda ranar alƙiyama za ta kasance da yadda za ta cika da abubuwan tsoro da tashin hankali. Ya bayyana cewa mushirikai suna tambayar Manzon Allah game da duwatsu; yaya za su kasance a ranar alƙiyama? Sai ya umarce shi da ya ba su amsa da cewa, Ubangijinsa zai tuttunɓuke su daga wurarensu ya kuma niƙe su tilis sannan ya sheƙe ƙurarsu ta bi iska. Ƙasar da take ɗauke da su kuma ta koma fili fetal; ba tudu ba kwari babu sauran wani gini ko tsiro a kanta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a wannan rana ne mutane za su bi mai kiran su zuwa ga matattara, kowa da kowa dole ya bi shi, babu mai iya kauce masa. A lokacin tsoro da kwarjini na Allah Mai rahama zai lulluɓe kowa; babu mai iya ɗaga murya ya yi magana mai ƙarfi; muryoyi za su yi tsit babu abin da za ka ji sai dai raɗa can ƙasa wadda ba ma a fahimtar abin da ake cewa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar musu da cewa, a wannan ranar babu wani wanda cetonsa zai yi amfani sai wanda Allah Mai rahama ya ba shi izinin yin ceton, kuma ya yarda ya yi magana a kan haka. Allah kuma yana sane da abin da yake gaban mutane na lamarin lahira, da kuma abin da suka baro a baya na al'amuran duniyarsu, amma bayinsa babu abin da suka sani game da Zatinsa da siffofinsa. Sai kuma ya bayyana yadda mutane a ranar za su kasu gida biyu da sakamakon kowane kashi. Fuskokin bayi za su ƙaskanta a gaban Allah Rayayye kuma Tsayayye da Zatinsa, wanda rayuwarsa ba ta da farko kuma ba ta da ƙarshe; shi ne mai gudanar da duk lamuran bayinsa. Kason mutane na farko a ranar su ne azzalumai waɗanda suka ƙi yin imani da Allah su yi ayyuka na ƙwarai, suka mutu da tarin zunubai. Allah ya bayyana cewa irin waɗannan mutane sun taɓe a wannan rana domin za su gamu da mummunan sakamakon ayyukansu.
Sai kuma kashi na biyu, su ne waɗanda suka yi kyawawan ayyuka bayan sun yi imani da Allah da manzanninsa. To duk wanda ya zamanto cikin wannan kaso, ba zai ji tsoron wani zalunci ba a ranar, watau ba za a azabtar da shi da laifin da bai aikata ba, haka kuma ba zai ji tsoron a yi masa ƙwauron ladansa ba, watau a rage masa wani abu daga kyawawan ayyukansa. A maimakon haka ma sai dai a riɓanya masa ladan kyawawan ayyukansa a kuma gafarta masa kurakuransa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani littafi ne da aka saukar da shi da harshen Larabci, don haka ba wanda zai fahimce shi cikakkiyar fahimta sai wanda ya koyi wannan harshe ya san asiran da ke ƙunshe cikinsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sarrafa bayanai na tsoratarwa da gargaɗi ta fuskoki daban-daban a Alƙur'ani; wani lokaci ya faɗi sunayensa masu nuna cikar adalcinsa da uƙubarsa ga masu laifi; wani lokaci kuma ta bayanin azabar da ya saukar wa al'ummun farko yayin da suka ƙaryata manzanninsa; wani lokaci kuwa ta hanyar mummunan tasirin da zunubbai suke haddasawa a cikin al'umma; wani sa'in kuma ya yi bayanin abubuwan ban tsoro da za su auku a ranar alƙiyama; sannan wani lokacin ta hanyar ambaton Jahannama da nau'o'in azabar da ke cikinta. Duk Allah ya yi haka ne domin nuna rahamarsa ga bayinsa don kuma su ji tsoronsa su yi aiki da umarninsa da kauce wa haninsa.

3. Babu wani abu da Allah ya umarci Annabi da ya roƙi Allah ƙarinsa sai ilimi. Wannan yana nuna girma da muhimmancin ilimi mai amfani a rayuwar Musulmi.

Suratu Ɗa Ha (113-114)
وَكَذَٰلِكَ أَنزَلۡنَٰهُ قُرۡءَانًا عَرَبِيّٗا وَصَرَّفۡنَا فِيهِ مِنَ ٱلۡوَعِيدِ لَعَلَّهُمۡ يَتَّقُونَ أَوۡ يُحۡدِثُ لَهُمۡ ذِكۡرٗا ١١٣ فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ ٱلۡمَلِكُ ٱلۡحَقُّۗ وَلَا تَعۡجَلۡ بِٱلۡقُرۡءَانِ مِن قَبۡلِ أَن يُقۡضَىٰٓ إِلَيۡكَ وَحۡيُهُۥۖ وَقُل رَّبِّ زِدۡنِي عِلۡمٗا ١١٤

113. Kuma kamar haka Muka saukar da shi (Alƙur'ani) Balarabe (watau da harshen Larabci), Muka kuma sarrafa ayoyin gargaɗi a cikinsa don su kiyaye dokokin (Allah) ko kuma ya sa su su wa'azantu.

114. Kuma fa Allah Sarki na gaskiya Ya ɗaukaka (daga maganganun kafirai). Kada kuma ka yi garaje da (karatun) Alƙur'ani tun kafin a gama yi maka wahayinsa, kuma ka ce: "Ubangiji Ka ƙara min ilimi."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda ya saukar da ayoyin da suka yi bayani a kan ranar lahira da tsorace-tsoracenta, to hakanan ya saukar da Alƙur'ani da harshen Larabci mai cike da fasaha da azancin magana, kuma mai ƙunshe da gargaɗi da narko iri-iri don ya sa musu taƙawa da tsoron Allah a zukatansu, su wa'azantu su daina aikata laifuffukan da suke yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tuna musu girmansa da ɗaukakarsa, da cewa ya ɗaukaka ya tsarkaka, shi ne Sarki mamallakin kowa da komai, kuma shi ne gaskiya kuma maganarsa ma gaskiya ce. Ya tsarkaka daga duk wata tawaya da mushirikai suke danganta shi da ita.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nusar da Annabi (ﷺ) yadda ya kamata ya yi wajen sauraron Mala'ika Jibrilu, ya hana shi yin garaje wajen bibiyar duk wata kalma da take fitowa daga Mala'ika Jibrilu idan yana karanta masa Alƙur'ani. Annabi yana gaggawa ne don gudun kada ya manta wani abu na Alƙur'ani, sai Allah ya hana shi yin haka, ya kuma umarce shi da ya yi shiru ya saurara har Mala'ikan ya gama karanta masa, shi kuma Allah shi ne zai tattara masa duk wannan karatu da ya ji a ƙirjinsa ba zai manta ko harafi ɗaya ba har sai ya isar da shi ga al'ummarsa. Allah kuma ya umarce shi da ya ci gaba da roƙon Allah kan ya ƙara masa ilimi.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Ku roƙi Allah ilimi mai amfani, kuma ku nemi tsarinsa daga ilimi marar amfani." [Ibn Majah #3843 da Ibn Hibban #82].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zurriyyar Annabi Adamu sun gaji mantuwa wajensa, don haka ne suke mantuwa kamar yadda ya yi mantuwa.

2. Yayin da ƙarfin himmar Annabi Adamu ya raunana sai ya bi hanyar da Allah ya hana shi ya bi, to amma nan da nan sai ya juyo ya dawo zuwa ga Ubangijinsa, ya tuba ya nemi gafararsa, Allah kuwa ya gafarta masa. Duk wanda ya ɗauki halin mahaifinsa to bai yi ɓarna ba.

3. Falalar tuba zuwa ga Allah. Bayan Annabi Adamu ya tuba sai darajarsa a wurin Allah ta ƙaru ya zama zaɓaɓɓensa ya kuma sake shiryar da shi.

4. Wajibi ne duk wasu ma'aurata kada su manta cewa babban maƙiyinsu shi ne Shaiɗan, don haka kada su ba shi damar ya ruguza musu jin daɗin zamantakewarsu ta aure.

5. Samar wa da ɗan'adam abinci yana gaba da buƙatarsa ta kayan sawa, don haka Allah ya fara bayyana kyautar ni'imar abinci ga Adamu kafin ta sutura.

6. Rashin wadar zuci game da arziƙin da Allah ya yi wa bawansa da kuma kwaɗayin tsawon rai suna daga cikin ƙofofin da Shaiɗan yake shigo wa bawa.

7. Yi ƙoƙari ka san halayen mutumin da za ka riƙa sauraren maganarsa.

8. Riƙo da karantarwar Alƙur'ani shi ne hanyar samun kyakkyawar rayuwa a duniya da lahira; kauce wa karantarwarsa kuwa hanya ce ta shiga ƙunci da azaba a rayuwar duniya da ta lahira.

9. Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) yana cewa: "Allah ya lamunce wa wanda ya karanta Alƙur'ani ya yi aiki da shi cewa ba zai ɓace ba a nan duniya, ba kuma zai wahala ba a lahira." [Dubi *Alƙurɗubi,* Juzu'i na 14, shafi na 156].

10. Duk wanda ya bijire wa karantarwar Allah to ba shi babu samun nutsuwa ko yalwar ƙirji a duniya, zai rayu ne cikin ƙuncin ɓata, ko da kuwa za a ga alamun jin daɗi a zahirinsa, yana saka tufafin da ya ga dama ya ci abin da ya so, ya zauna inda ya so; zuciyarsa za ta ci gaba da rayuwa cikin damuwa da ɗimuwa, ba za su rabu da shi ba har sai ya shiriya ya komo ga Allah mahaliccinsa.

Suratu Ɗa Ha (115-127)

وَلَقَدۡ عَهِدۡنَآ إِلَىٰٓ ءَادَمَ مِن قَبۡلُ فَنَسِيَ وَلَمۡ نَجِدۡ لَهُۥ عَزۡمٗا ١١٥ وَإِذۡ قُلۡنَا لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ ٱسۡجُدُواْ لِأٓدَمَ فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبۡلِيسَ أَبَىٰ ١١٦ فَقُلۡنَا يَٰٓـَٔادَمُ إِنَّ هَٰذَا عَدُوّٞ لَّكَ وَلِزَوۡجِكَ فَلَا يُخۡرِجَنَّكُمَا مِنَ ٱلۡجَنَّةِ فَتَشۡقَىٰٓ ١١٧ إِنَّ لَكَ أَلَّا تَجُوعَ فِيهَا وَلَا تَعۡرَىٰ ١١٨ وَأَنَّكَ لَا تَظۡمَؤُاْ فِيهَا وَلَا تَضۡحَىٰ ١١٩ فَوَسۡوَسَ إِلَيۡهِ ٱلشَّيۡطَٰنُ قَالَ يَٰٓـَٔادَمُ هَلۡ أَدُلُّكَ عَلَىٰ شَجَرَةِ ٱلۡخُلۡدِ وَمُلۡكٖ لَّا يَبۡلَىٰ ١٢٠ فَأَكَلَا مِنۡهَا فَبَدَتۡ لَهُمَا سَوۡءَٰتُهُمَا وَطَفِقَا يَخۡصِفَانِ عَلَيۡهِمَا مِن وَرَقِ ٱلۡجَنَّةِۚ وَعَصَىٰٓ ءَادَمُ رَبَّهُۥ فَغَوَىٰ ١٢١ ثُمَّ ٱجۡتَبَٰهُ رَبُّهُۥ فَتَابَ عَلَيۡهِ وَهَدَىٰ ١٢٢ قَالَ ٱهۡبِطَا مِنۡهَا جَمِيعَۢاۖ بَعۡضُكُمۡ لِبَعۡضٍ عَدُوّٞۖ فَإِمَّا يَأۡتِيَنَّكُم مِّنِّي هُدٗى فَمَنِ ٱتَّبَعَ هُدَايَ فَلَا يَضِلُّ وَلَا يَشۡقَىٰ ١٢٣ وَمَنۡ أَعۡرَضَ عَن ذِكۡرِي فَإِنَّ لَهُۥ مَعِيشَةٗ ضَنكٗا وَنَحۡشُرُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ أَعۡمَىٰ ١٢٤ قَالَ رَبِّ لِمَ حَشَرۡتَنِيٓ أَعۡمَىٰ وَقَدۡ كُنتُ بَصِيرٗا ١٢٥ قَالَ كَذَٰلِكَ أَتَتۡكَ ءَايَٰتُنَا فَنَسِيتَهَاۖ وَكَذَٰلِكَ ٱلۡيَوۡمَ تُنسَىٰ ١٢٦ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي مَنۡ أَسۡرَفَ وَلَمۡ يُؤۡمِنۢ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦۚ وَلَعَذَابُ ٱلۡأٓخِرَةِ أَشَدُّ وَأَبۡقَىٰٓ ١٢٧

115. Kuma haƙiƙa Mun yi alƙawari da Adamu tun da farko (cewa kada ya ci itaciyar da aka hana shi), sai ya manta, sai ba Mu same shi da ƙarfin ƙuduri ba.

116. Kuma (ka tuna) lokacin da Muka ce da mala'iku: "Ku yi sujjada ga Adamu" sai suka yi sujjadar sai Iblis ne kawai ya ƙi.

117. Sannan Muka ce: "Ya Adamu, lalle wannan maƙiyinka ne kai da matarka, to kada (ku yarda) ya fitar da ku daga Aljanna, sai ka wahala.

118. "Lalle (Allah) Ya yi maka alƙawarin ba za ka ji yunwa ba a cikinta, kuma ba za ka yi tsiraici ba.

119. "Kuma lalle kai ba za ka ji ƙishi ba a cikinta, kuma ba za ka ji zafin rana ba."

120. Sai Shaiɗan ya yi masa waswasi ya ce: "Ya Adamu, yanzu ba na nuna maka wata bishiya ta dawwama da kuma mulki wanda ba zai ƙare ba?"

121. Sai suka ci wani abu daga gare ta, sai ga tsiraicinsu ya bayyana gare su, sai suka riƙa lulluɓe (jikinsu) da ganyen Aljanna. Kuma Adamu ya saba wa Ubangijinsa ya bar shiriya.

122. Sannan Ubangijinsa Ya zaɓe shi, sai Ya yafe masa Ya kuma shirye (shi).

123. (Allah) Ya ce (da Adamu da Hauwa'u): "Ku sauka daga gare ta (Aljannar) gaba ɗayanku, sashinku ya dinga gaba da sashi; sannan idan shiriya ta zo muku daga gare Ni, to duk wanda ya bi shiriyata ba zai taɓe ba, kuma ba zai wahala ba.

124. "Wanda kuma ya bijire wa Alƙur'ani to lalle zai yi rayuwa mai ƙunci, kuma Mu tashe shi makaho ranar alƙiyama."

125. Zai ce: "Ubangijina me ya sa Ka tashe ni makaho, alhali kuwa na kasance mai gani?"

126. (Allah) Ya ce: "Kamar haka ne ayoyinmu suka zo maka sai ka manta su, to kamar haka kuwa (kai ma) za a manta da kai a yau."

127. Kamar haka Muke saka wa (duk) wanda ya yi ɓarna kuma bai yi imani da ayoyin Ubangijinsa ba. Kuma azabar lahira tabbas ta fi tsanani ta kuma fi dawwama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya labarta mana ƙissar Annabi Adamu da matarsa Hauwa'u da abin da ya faru tsakaninsu da Iblis la'ananne. Allah ya tabbatar da cewa ya yi alƙawari da Adamu tun farko, kuma Annabi Adamu ya ƙuduri aniyar riƙe wannan alƙawari da aiki da shi; to amma daga baya sai ya manta. Allah ya tabbatar da cewa bai sami Adamu da ƙarfin ƙudiri ba, domin mantuwa wadda ɗabi'a ce ta ɗan'adam ita ce ta riske shi, don haka sai ya manta alƙawarin da suka yi da Ubangijinsa, ya faɗa cikin kuskure, amma daga baya ya tuba Allah kuma ya karɓi tubansa, ya sake ɗora kan hanyar shiriya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana abin da ya faru daki-daki da cewa, bayan ya halicci Adamu daga taɓo da hannunsa ya kuma busa masa rai, ya sanar da shi sunayen abubuwan amfaninsa, sai ya umarci mala'iku su girmama shi ta hanyar faɗuwa su yi masa sujjada. Mala'iku gaba ɗaya suka bi umarnin Allah suka faɗi suka yi wa Adamu sujjada in ban da Iblis, wanda shi ma yana cikinsu amma shi aljani ne ba mala'ika ba, sai ya yi girman kai ya ƙi yarda ya yi wa Adamu sujjada, da hujjar cewa shi ya fi shi matsayi, domin shi da wuta aka halicce shi, Adamu kuwa da taɓo Allah ya yi shi. To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Adamu da matarsa Hauwa'u cewa, Iblis fa babban maƙiyinsu ne mai yi musu hassada da ni'imar da Allah ya yi musu, don haka kada su yarda ya fitar da su daga gidan Aljanna, za su sha wahala.
Sai kuma ya bayyana wa Adamu da Hauwa'u tarin ni'imomin da ya shirya musu a gidan Aljanna, da cewa, ya yi musu tanadin abin da za su ci a cikinta ba za su taɓa jin yunwa ba, da kuma suturar da za su saka ba za su taɓa yin tsiraici ba, da kuma abin sha, don haka ba su ba ƙishi a cikinta, ga kuma inuwa mayalwaciya, ba su babu zafin rana. To sai dai kuma ya haramta musu kusantar wata bishiya guda ɗaya ta cikin Aljannar ya nuna musu illar cin 'ya'yanta. Amma kuma sai maƙiyinsu Iblis ya saɗaɗo ya shiga yi wa Adamu waswasi a ransa, ya nuna masa cewa zai nuna masa wata bishiya da idan ya ci 'ya'yanta zai dawwama a Aljanna, kuma ya sami mulki wanda ba zai yanke ba na har abada. Sai ko Adamu ya ruɗu da wannan waswasi na Iblis, domin ya zo masa a matsayin masoyinsa mai faɗa masa gaskiya har da haɗawa da rantsuwa da Allah a kan haka. Sai Adamu da Hauwa'u suka manta wancan alƙawari na farko tsakaninsu da Allah, wanda ya hana su cin wannan itaciya, sai kawai suka ci 'ya'yanta, nan take kuwa suturar da ke jikinsu ta zube, tsiraicinsu ya bayyana a fili, sai kuma kunyar Allah ta lulluɓe su sai suka fara tsinkar ganyen itatuwan Aljanna suna kare tsiraicinsu da shi. Sai Allah ya tunatar da Adamu cewa ya saba wa Ubangijinsa, ya saki hanyar shiriyar da ya ɗora shi a kanta tun farko. To amma sai suka yi gaggawa suka nemi tuba da afuwa daga Allah suka amasa laifinsu, sai kuwa Allah ya karɓi tubansu, ya ma zaɓi Adamu ya kuma sake ba shi shiriya, matsayinsa a wurin Allah ma ya dawo fiye da na farko. Iblis kuma ya juya da makircinsa bai yi nasara ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya umarci Adamu da Hauwa'u kan su sauko daga Aljanna zuwa bayan ƙasa, sannan su da Iblis za su ci gaba da zama abokan gabar juna. Ya kuma sanar da su cewa, idan wani bayani na tafarkin shiriya ya zo musu daga Allah, to su sani duk wanda ya bi wannan tafarkin ya yi aiki da shi bai kauce masa ba, to ba zai taɓe ba, ba kuma zai sha wahala ba a lahira, domin makomarsa Aljanna ce gidan hutu. To amma duk wanda ya kuskura ya bijire wa ayoyin Allah da shiriyarsa ya ƙi karɓar su, to zai fuskanci wata rayuwa mai ƙunci a nan duniya da kuma barzahu (watau a ƙabarinsa). Sannan kuma a ranar lahira a tashe shi don yi masa hisabi yana makaho dunɗum ba ya ganin komai.
Anan zai yi ta sallallami yana kururuwa yana tambayar Ubangiji me ya sa ya tashe shi makaho alhali a duniya yana gani tar? Sai Allah ya ba shi amsa da cewa, haka shi ma ya yi a duniya lokacin da ayoyin Allah suka zo masa, an karanta masa dokokin Allah to amma sai ya yi watsi da su. To hakanan shi ma a lahira za a yi watsi da shi. Irin aikinsa ya yi daidai da irin sakamakonsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, irin wannan mummunan sakamakon yake jiran duk wani wanda ya faɗa dumu-dumu cikin aikata laifuka a duniya, ya ƙi yin imani da ayoyin Ubangijinsa bayyanannu. Sai kuma ya ƙara tabbatar da cewa azabar lahira fa ta fi tsanani da muni fiye da rayuwa mai ƙunci ta duniya da barzahu, domin ita ce mai dawwama har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu mai gane ayoyin Allah ya wa'azantu da su sai mai lafiyayyen hankali kawai.

2. Yawan tasbihi tare da godiya da kirari ga Allah safe da yamma yana taimaka wa bawa wajen gusar masa da damuwa da baƙin ciki.

3. Idan bawa ya kula da cewa zuciyarsa ta ta'allaƙa sosai da sha'anin duniya da ƙyalƙyalinta to ya auna tsakanin daɗinta mai gushewa da kyakkyawan sakamako na lahira mai ɗorewa.

4. Idan ka ga Allah ya fifita wani a kanka cikin sha'anin duniya, to kai kuma ka dubi yadda ya fifita ka a kansa a cikin sha'anin lahira.

5. Idan an nemi mumini da ya umarci iyalansa su tsayar da salla, to wannan yana nufin lalle ya tabbata ya koyar da su abin da sallar za ta tsayu da shi na sanin rukunanta da wajibanta da sharuɗɗanta.

6. Kula da addini musamman salla da umartar iyali da kula da shi yana daga cikin hanyoyin samun arziƙi daga Allah.

7. Ko kaɗan bai dace ba a ce neman arziƙi ya sanya Musulmi ya manta da tsayar da salla a kan lokacinta kuma yadda ya dace, domin arziƙin kowa yana hannun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Ɗa Ha (128-132)

أَفَلَمْ يَهْدِ لَهُمْ كَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّنَ ٱلْقُرُونِ يَمْشُونَ فِى مَسَٰكِنِهِمْ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّأُو۟لِى ٱلنُّهَىٰ ﴿١٢٨﴾ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ مِن رَّبِّكَ
لَكَانَ لِزَامًا وَأَجَلٌ مُّسَمًّى ﴿١٢٩﴾ فَٱصْبِرْ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ قَبْلَ طُلُوعِ ٱلشَّمْسِ وَقَبْلَ غُرُوبِهَا ۖ وَمِنْ ءَانَآئِ ٱلَّيْلِ فَسَبِّحْ
وَأَطْرَافَ ٱلنَّهَارِ لَعَلَّكَ تَرْضَىٰ ﴿١٣٠﴾ وَلَا تَمُدَّنَّ عَيْنَيْكَ إِلَىٰ مَا مَتَّعْنَا بِهِۦٓ أَزْوَٰجًا مِّنْهُمْ زَهْرَةَ ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا لِنَفْتِنَهُمْ فِيهِ ۚ وَرِزْقُ رَبِّكَ خَيْرٌ
وَأَبْقَىٰ ﴿١٣١﴾ وَأْمُرْ أَهْلَكَ بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱصْطَبِرْ عَلَيْهَا ۖ لَا نَسْـَٔلُكَ رِزْقًا ۖ نَّحْنُ نَرْزُقُكَ ۗ وَٱلْعَٰقِبَةُ لِلتَّقْوَىٰ ﴿١٣٢﴾

128. Yanzu (mutanen Makka) ba su gane cewa al'ummu nawa muka hallaka a gabaninsu ba waɗanda suna wucewa ta gidajensu? Lalle a game da wannan akwai ayoyi ga ma'abota hankali.

129. Ba don kuwa wata kalma da ta rigaya daga Ubangijinka ba, da kuma wani wa'adi ƙayyadajje, to da (azaba) ta zama dole (a kansu tun a duniya).

130. Sai ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, kuma ka yi tasbihi da godiyar Ubangijinka kafin hudowar rana, da kuma gabanin faɗuwarta; a (wasu) lokatai na dare kuma ka yi tasbihi, da kuma gefukan wuni don (a saka maka da abin da) za ka yarda.

131. Kada kuma ka zura idanuwanka a kan dangogin daɗin da Muka jiyar da wasu daga cikinsu, na adon rayuwar duniya ne don Mu jarrabe su da shi. Arzikin Ubangijinka kuwa (shi) ya fi alheri ya kuma fi dawwama.

132. Ka kuma umarci iyalinka da (tsai da) salla, kuma ka dawwama a kanta; ba Ma neman ka arzuta (kanka da iyalinka); Mu ne za Mu arzuta ka. Kyakkyawan ƙarshe kuwa yana ga masu taƙawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai abin da za su wa'azantu da shi da a ce sun yi aiki da hankulansu. Wannan kuwa shi ne yawan al'ummun da Allah ya hallaka gabaninsu waɗanda suna wucewa ta gidajensu suna ganin irin yadda Allah ya yi da su. To amma ba kowa ne zai ɗauki izina da darasi daga hakan ba sai masu lafiyayyun hankula.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Annabi cewa, ba don ya riga ya yi alƙawarin cewa ba zai azabtar da kowa ba har sai ya tsayar masa da hujja, da kuma ajali na rayuwa da ya riga ya ƙayyade wa kowa a duniya ba, to ba don haka ba da ya gaggauto azabarsa ga kafiran nan masu ƙaryata Manzonsa (ﷺ), ya hallaka su kamar yadda ya hallaka kafiran da suka gabace su, domin sun cancanci ya yi musu haka. To amma ba zai yi musu azaba ta gaba ɗaya ba.
Sai ya umarci Annabi (ﷺ) da yin haƙuri game da ƙaryatawar da kafirai suke yi masa da miyagun maganganu da munanan siffofin da suke siffanta shi da su. Ya kuma umarce shi da tsarkake Ubangijinsa da gode masa a cikin sallar Asuba gabanin hudowar rana da sallar La'asar kafin faɗuwar rana, da sallar Magariba da Isha'i a cikin sa'o'in dare, da kuma sallar Azahar lokacin da rana ta yi zawali gefen yini na farko da sallar Magariba bayan ƙarewar gefensa na biyu, da fatan ya samu sakamakon ladan da zai yarda da shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi Manzonsa da kada ya zura ido ga dangogin kayayyakin jin daɗi na ƙyale-ƙyalen duniya da ya ba wa kafirai masu ƙaryata shi, domin ya jarrabe su da shi, ya sanar da shi cewa, duk abin da ya ba su mai gushewa ne, amma abin da ya yi masa alƙawari na kyakkyawan sakamako shi ne mafi alheri kuma dawwamamme, ba zai yanke ba har abada.
Lokacin da Sayyidina Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya shiga shigifar Manzon Allah (ﷺ) bayan ya ƙaurace wa matansa na tsawon wata guda, ya same shi kwance a kan wata karaunin tabarma. Ban da wata salka ta fata a rataye Umar bai hango komai na jin daɗi a wannan shigifa ta Manzon Allah (ﷺ) ba, sai kawai ya fashe da kuka. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya tambaye shi abin da ya saka shi kuka, sai ya kada baki ya ce: "Ya Ma'aikin Allah, dubi irin rayuwar da Kisra da Kaisara suke ciki, ga ka kai kuma zaɓaɓɓen Allah cikin halittunsa, duba ka ga irin yadda kake rayuwa." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kana da wata shakka ne ya ɗan Khaɗɗab? Waɗancan ai su wasu mutane ne da aka gaggauto musu jin daɗinsu tun a nan duniya." [Bukhari #2468 da Muslim #1479].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) cewa ya umarci iyalansa da tsai da salla, shi ma kuma ya dage wajen kulawa da ita, Allah ya tabbatar masa da cewa ba ya neman sa da ya arzuta kansa ko iyalansa da abinci ko abin sha; Allah ne da kansa ya ɗauke masa wannan nauyin, shi zai hore

masa arziƙinsa da na iyalansa. Kuma ya sani cewa kyakkyawan ƙarshe a duniya da lahira yana ga masu tsoron Allah, watau masu aikata umarninsa suna kuma kauce wa haninsa.

An karƀo daga Abdullahi ɗan Amru ɗan Asi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku umarci 'ya'yanku ƙanana da salla idan sun cika shekara bakwai, kuma ku doke su a kan barin ta idan sun cika shekara goma, ku kuma raba tsakanin (mazansu da matansu) a wajen kwanciya." [Ahmad #6689 da Abu Dawud #496].

An karƀo daga Ma'aƙilu ɗan Yasar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ubangijinku yana cewa: 'Ya kai ɗan'adam, ka ba da lokacinka wajen bauta mini zan cika maka zuciya da wadata, zan kuma cika maka hannayenka da arziƙi. Ya kai ɗan'adam, kada ka yi nisa da ni sai in cika maka zuciya da talauci, in kuma cika maka hannaye da shagulgula.'" [Hakim, *Al-Mustadrak*, Juzu'i na 4, shafi na 326].

An karƀo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wata rana na yi mafarki da daddare muna zaune a gidan Uƙubatu ɗan Rafi'u sai aka kawo mana dabino lubiya daga dabinon gonar Ibn Ɗab, sai na fassara mafarkin da cewa, mu ne masu ɗaukaka a nan duniya, kuma masu kyakkyawan ƙarshe a lahira, kuma addininmu ya yi kyau." [Muslim #2270].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babbar mu'ujiza da Allah ya ba wa Manzo (ﷺ) ita ce Alƙur'ani, domin ita ce mai wanzuwa har zuwa ƙarshen duniya. Ko da yake Allah ya ba shi wasu mu'ujizoji masu yawa, amma amfaninsu ya taƙaita ne a zamaninsa kawai.

2. Kafirai waɗanda Allah ya riga ya toshe musu zuciya ba wata aya da za ta amfane su domin su shiriya.

3. Allah ba ya azabtar da bayinsa sai ya tsayar musu da hujja ta hanyar aiko da manzo don ya isar musu da saƙonsa. Duk wanda saƙon nan ya kai gare shi, to an yanke masa duk wani hanzari ranar alƙiyama.

Suratu Ɗa Ha (133-135)
وَقَالُواْ لَوۡلَا يَأۡتِينَا بِـَٔايَةٖ مِّن رَّبِّهِۦٓۚ أَوَ لَمۡ تَأۡتِهِم بَيِّنَةُ مَا فِي ٱلصُّحُفِ ٱلۡأُولَىٰ ١٣٣ وَلَوۡ أَنَّآ أَهۡلَكۡنَٰهُم بِعَذَابٖ مِّن قَبۡلِهِۦ لَقَالُواْ رَبَّنَا لَوۡلَآ أَرۡسَلۡتَ إِلَيۡنَا رَسُولٗا فَنَتَّبِعَ ءَايَٰتِكَ مِن قَبۡلِ أَن نَّذِلَّ وَنَخۡزَىٰ ١٣٤ قُلۡ كُلّٞ مُّتَرَبِّصٞ فَتَرَبَّصُواْۖ فَسَتَعۡلَمُونَ مَنۡ أَصۡحَٰبُ ٱلصِّرَٰطِ ٱلسَّوِيِّ وَمَنِ ٱهۡتَدَىٰ ١٣٥

133. Suka kuma ce: "Me ya sa bai zo mana da wata aya daga Ubangijinsa ba?" Yanzu hujjar abin da yake cikin littattafan farko ba ta zo musu ba (wato Alƙur'ani)?

134. In da a ce Mun hallaka su ne da azaba tun gabaninsa (wato Annabi Muhammadu), to da sun ce: "Ubangijinmu, me ya sa ba Ka aiko mana da wani manzo ba sai mu bi ayoyinka tun kafin mu ƙaskanta mu kuma wulaƙanta?"

135. Ka ce (da su): "Kowanne (ni da ku) mai sauraro ne, sai ku saurara; to ba da daɗewa ba za ku san su wane ne ma'abota hanya madaidaiciya, kuma su wane ne suke kan shiriya."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin ƙalubalantar da kafirai suka riƙa yi wa Annabi (ﷺ) na cewa, me ya sa bai kawo musu wata hujja mai ƙarfi daga Allah ba wadda za ta tabbatar musu da cewa shi da gaske annabin Allah ne. Sai Allah ya mayar musu da martani cewa, ashe Alƙur'ani bai zo musu ba wanda yake gaskata littattafan da suka gabace shi, watau wannan bai ishe su hujja ba a kan gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ)?

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani annabi sai da aka ba shi mu'ujizar da mutane suka yi imani da shi saboda ita. Amma ni mu'ujizar da aka ba ni wahayi ne wanda aka yi min (watau Alƙur'ani), ina fatan in fi su yawan mabiya a ranar alƙiyama." [Bukhari #4981 da Muslim #231].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa da ya hallaka su da wata azaba kafin ya aiko musu Manzon Allah (ﷺ) ya karanta musu ayoyin Alƙur'ani ya gargaɗe su, to a ranar lahira idan Allah ya titsiye su a gabansa da za su ce, me ya sa bai aiko musu da manzo ba a duniya; ai da ya aiko musu manzo da sun yi imani da shi, sun yarda da abin da ya zo da shi, kafin wannan rana ta lahira ta zo su wulaƙanta su kunyata saboda azabar da za su gamu da ita.
Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) ya sanar da kafirai cewa shi da su duka suna nan suna sauraron abin da Allah zai yi da su, don haka su ma su ci gaba da sauraro, tabbas ba da jimawa ba za su san su wane ne suke kan miƙaƙƙiyar hanya kuma su wane ne a kan shiriya, Musulmi ko su?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya sakankance game da kusantowar alƙiyama, to lallai za a same shi da ƙarancin guri, zai kuma yawaita tuba ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai karkata ɗungurungum zuwa ga duniya ba.

2. Kusantowar hisabi ga mutane yana ɗauke da ma'anoni guda biyu:
Ma'ana ta farko, wannan al'ummar ita ce ƙarshen al'ummu, kuma manzonta shi ne manzo na ƙarshe, kuma daga kan al'ummarsa ne alƙiyama za ta tsaya. Don haka bisa la'akari da wannan ne za a ce alƙiyama ta matso kusa. Annabi (ﷺ) ya ce: "An aiko ni tsakanina da tashin alƙiyama kamar 'yan yatsun nan ne." Sai ya nuna yatsarsa manuniya da ta kusa da ita. [Bukhari #6505 da Muslim #2951].
Ma'ana ta biyu, manufar kusantowar hisabi ita ce mutuwa; duk wanda ya mutu to alƙiyamarsa ta riga ta tsaya ke nan ya shiga gidan hisabi.

3. Kafirai sun riƙa ganawa da juna a ɓoye suna maganganu na suka ga Annabi (ﷺ) da Alƙur'ani, don wai kada Manzon Allah (ﷺ) ya san abin da suke ƙullawa har ya ƙalubalance su da martani. Ko kuma suna ganawa ne da wasu waɗanda suka lura suna da alamun sun fara yarda da Annabi (ﷺ) don su jefa musu shakka a kansa.

4. Tufka da warwarar maganganun kafirai a kan lamarin Manzon Allah (ﷺ) da Alƙur'ani, babbar hujja ce da ke nuna rashin gaskiyarsu da rikicewar al'amuransu.

5. Daga cikin hikimomin da suka sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai biya wa mushirikan Makka buƙatarsu ba ta a nuna musu wata mu'ujiza irin ta annabawan farko shi ne domin ba ya nufin hallaka su kamar yadda ya hallaka na farko; yana nufin samar da wata zurriyya daga tsatsonsu waɗanda su ne za su karɓi wannan addinin su kuma yaɗa shi ko'ina a duniya. Haka kuwa abin ya kasance daga ƙarshe.

6. Yana daga cikin aƙidar Ahlussunna cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai gushe ba yana magana. Yana magana da wanda ya so, a sanda ya so, a inda ya so.

21-Suratul Anbiya

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna *Suratul Anbiya*.

An karƀo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "*Suratu Banu Isra'ila* da *Al-Kahafi* da *Maryam* da *Ƭaha* da *Al-Anbiya* suna cikin tsohuwar haddata ta farko." [Bukhari #4708].

An kirawo ta da wannan suna '*Al-Anbiya*' saboda an ambaci labaran annabawa da yawa a cikinta fiye da kowace sura a Alƙur'ani. Ko da kuwa '*Suratul An'am'* an ambaci sunaye ne kawai na annabawa goma sha takwas, amma 'yan kaɗan ne aka ambaci tarihinsu a cikinta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Ra'ayin malamai ya haɗu a kan cewa Sura ce *Makkiyya.*

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta saba'in da ɗaya (71) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan *Suratus Sajda* kafin *Suratun Nahli*, don haka tana daga cikin surori na ƙarshe-ƙarshen sauka kafin Hijira.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta a lissafin mutanen Makka da Madina da Sham da Basra ɗari da goma sha ɗaya ne (111). Amma a lissafin mutanen Kufa kuwa ɗari da goma sha biyu ne (112).

5. Babban Jigonta:
Bayanin cewa da'awar annabawa da karantarwarsu guda ce. Dukkansu sun yi kira ne zuwa ga bautar Allah shi kaɗai ba tare da yi masa shirka ba.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Gargaɗi game da kusantowar tashin alƙiyama.
• Bayani a kan cewa Manzon Allah ((ﷺ kamar sauran manzanni ne da Allah ya aiko gabaninsa; ya zo ne da addini kwatankwacin irin wanda suka zo da shi.
• Bayani game da girman sha'anin Alƙur'ani da kasancewarsa ni'ima da ɗaukaka ga wannan al'umma idan sun yi riƙo da shi.
• Gargaɗi game da azabar Allah wadda ya saukar a kan al'ummun da suka gabata bayan sun ƙaryata manzanninsu, kuma shi mai iya saukar wa da wannan al'umma azabarsa ne idan sun doge a kan kafirci.
• Bayani game da halittar sammai da ƙasa da abin da suka ƙunsa na dalilai game da Kaɗaitakar mahaliccinsu da tsarkake shi daga ababen tarayya.

• Ambaton tarihin wasu annabawa da suka gabata da su ma suka zo da irin saƙon da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi na Tauhidi da ƙalubale da suka fuskanta daga al'ummunsu kamar yadda shim a ya fuskanta, amma daga ƙarshe Allah ya ba su nasara a kan maƙiyansu.
• Bayani game da cewa kyakkyawan ƙarshe yana ga muminai a duniya da lahira. Kuma Allah zai yi hukunci tsakanin ɓangarorin biyu hukunci na gaskiya.

Suratul Anbiya (1-6)
ٱقۡتَرَبَ لِلنَّاسِ حِسَابُهُمۡ وَهُمۡ فِي غَفۡلَةٖ مُّعۡرِضُونَ ١ مَا يَأۡتِيهِم مِّن ذِكۡرٖ مِّن رَّبِّهِم مُّحۡدَثٍ إِلَّا ٱسۡتَمَعُوهُ وَهُمۡ يَلۡعَبُونَ ٢ لَاهِيَةٗ قُلُوبُهُمۡۗ وَأَسَرُّواْ ٱلنَّجۡوَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ هَلۡ هَٰذَآ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡۖ أَفَتَأۡتُونَ ٱلسِّحۡرَ وَأَنتُمۡ تُبۡصِرُونَ ٣ قَالَ رَبِّي يَعۡلَمُ ٱلۡقَوۡلَ فِي ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٤ بَلۡ قَالُوٓاْ أَضۡغَٰثُ أَحۡلَٰمِۭ بَلِ ٱفۡتَرَىٰهُ بَلۡ هُوَ شَاعِرٞ فَلۡيَأۡتِنَا بِاٰيَةٖ كَمَآ أُرۡسِلَ ٱلۡأَوَّلُونَ ٥ مَآ ءَامَنَتۡ قَبۡلَهُم مِّن قَرۡيَةٍ أَهۡلَكۡنَٰهَاۖ أَفَهُمۡ يُؤۡمِنُونَ ٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Lokacin yi wa mutane hisabi ya kusanto, alhali suna cikin gafala (suna) masu bijirewa.

2. Ba wata tunatarwa sabowa (wato Alƙur'ani) da za ta zo musu daga Ubangijinsu face sai sun saurare ta suna masu wasa.

3. Zukatansu suna cikin gafala. Waɗanda suka yi zalunci kuma suka ɓoye abin da suka tattauna (na cewa): "Wannan ba wani ne in ban da mutum kamarku; yanzu kwa riƙa bin sihiri alhali kuwa ku kuna gani?"

4. Ya ce: "Ubangijina Yana sane da (kowace) magana a cikin sammai da ƙasa; Shi kuwa Mai ji ne, Masani.

5. A'a, cewa dai suka yi: "Ai (shi Alƙur'ani) tarkacen mafarki ne, a'a, shi (Muhammadu) ƙago shi ya yi, a'a, shi mawaƙi dai ne, to sai ya zo mana da wata aya kamar yadda aka aiko wa mutanen farko."

6. Ai babu wata al'umma da ta yi imani a gabaninsu wadda Muka hallaka; shin yanzu su za su yi imani?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da bayanin wani hali mai ban al'ajabi na mutane, watau yadda suka gafala suke bijirewa bayan ga shi ranar yi musu hisabin ayyukansu tana ta ƙara matsowa, watau ranar alƙiyama, amma sun shagala da duniya da ƙyale-ƙyalenta.
Sai kuma ya bayyana irin yadda suke bijire wa wa'azi da kiran da ake yi musu, da cewa duk wani abu sabo daga Alƙur'ani da ya sauka daga Ubangijinsu don tunatar da su da gargaɗin su sai su saurare shi sauraro marar amfani, domin za su ɗauke shi ne abin wasa ba na gaske ba. Sukan saurare shi zukatansu suna cike da gafala, ban da duniya babu abin da yake gabansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da kafirai azzalumai suke haɗuwa suna ganawa a kansa, suna tattaunawa da junansu, har ma wasu daga cikinsu suna cewa, wai shi wannan mutum da yake cewa shi Manzon Allah ne ba mutum ne irinsu ba; da me shi ya fi su har da zai yi da'awar manzanci? Sannan su zarge shi da cewa abin da ya zo da shi sihiri ne, sai su ja kunnuwan junansu a kan su nisanci bin sa bayan sun fahimci shi mutum ne kawai kamarsu, kuma sihiri ne ya zo musu da shi ba gaskiya ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya mayar musu da martani a kan waɗannan miyagun maganganu da suke tattaunawa a ɓoye da cewa, Ubangijinsa yana sane da duk wata magana ta sarari da ta ɓoye, a cikin sammai da ƙasa, domin shi mai jin duk maganganun bayinsa ne, kuma masanin duk ayyukansu, don haka zai yi musu sakayya a kansu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu irin maganganu na kafirai a kan Manzon Allah (ﷺ) waɗanda suke ƙara tabbatar da rashin gaskiyarsu da kuma rashin wata takamaimiyar hujja da suke dogara a kanta wajen ƙaryata shi. Wasu daga cikinsu suka ce abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da shi wasu kwashe-kwashen mafarki ne wanda ba ya da wata fassara ta gaskiya, wani lokaci kuma sai suka ce ai shi ne yake ƙagar maganganun da kansa waɗanda ba su da wani tushe yana jingina wa Allah. Wani lokaci kuma su ce masa mawaƙi. Wannan tubka-da-warwara tana nuna rashin madafar zancensu, sai shaci-faɗi da son zuciya kawai. Har ma suka ƙalubalance shi da cewa, idan har da gaske shi Manzon Allah ne to ya nuna musu wata mu'ujiza irin ta manzannin farko da Allah ya aiko, kamar sanda ta Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ko taguwar Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su amsa da cewa, duk al'ummun da suka gabace su waɗanda suka nemi annabawansu da su kawo musu wasu mu'ujizoji, to bayan sun kawo musu su ai bijire musu suka yi ba su yi imani da su ba, daga ƙarshe kuma Allah ya hallaka su. To shin su yanzu waɗannan da suke neman su ma a zo musu da mu'ujiza za su yi imani ne da ita idan ta zo? Watau dai su ma za su yi irin abin da waɗancan suka yi ne, ba za su yi imanin ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya aiko maza ne a matsayin manzanni ba mata ba.

2. Wajibi ne a kan duk wanda bai san hukuncin Allah ba ya tambayi wanda ya sani domin ya sanar da shi.

3. Wajibi ne a kan malamai su karantar da mutane addininsu. Idan kuma an tambaye su abin da suka sani to dole ne su ba da amsa a kai.

4. Abin da yake wajibi a kan gama-garin mutane shi ne tambayar malamai da aiki da fatawoyinsu.

5. Annabawa mutane ne da Allah ya zaɓa ya yi musu wahayi. Annabcinsu bai fitar da su daga ɗabi'a ta mutane ba; suna ci suna sha suna aure suna hayayyafa da sauran abubuwan da suke bijiro wa 'yan'adam.

6. Babu ta inda wannan al'umma za ta sami ɗaukaka da daraja sai ta hanyar riƙo da karantarwar Alƙur'ani. Riƙo da al'ummar farko suka yi wa Alƙur'ani shi ne ya sa suka sami ɗaukaka da nasarori masu yawa a kan abokan gabansu. Watsi da Alƙur'ani da wannan al'umma suka yi shi ne ya jawo musu ƙaskanci da tozarta a rayuwarsu.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tare da manzanninsa da mabiyansu da taimakonsa da nasararsa.

Suratul Anbiya (7-10)
وَمَآ أَرۡسَلۡنَا قَبۡلَكَ إِلَّا رِجَالٗا نُّوحِيٓ إِلَيۡهِمۡۖ فَسۡـَٔلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلذِّكۡرِ إِن كُنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ ٧ وَمَا جَعَلۡنَٰهُمۡ جَسَدٗا لَّا يَأۡكُلُونَ ٱلطَّعَامَ وَمَا كَانُواْ خَٰلِدِينَ ٨ ثُمَّ صَدَقۡنَٰهُمُ ٱلۡوَعۡدَ فَأَنجَيۡنَٰهُمۡ وَمَن نَّشَآءُ وَأَهۡلَكۡنَا ٱلۡمُسۡرِفِينَ ٩ لَقَدۡ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكُمۡ كِتَٰبٗا فِيهِ ذِكۡرُكُمۡۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ١٠

7. Kuma ba Mu aiko (wasu manzanni) gabaninka ba sai mazaje da Muke yi musu wahayi; to ku tambayi ma'abota sani idan ya zamana ku ba ku sani ba.

8. Kuma ba Mu sanya su jiki ne da ba sa cin abinci ba, kuma ba su zamanto masu dawwama ba.

9. Sannan Muka cika musu alƙawari, sai Muka tserar da su da waɗanda Muke ga damar (tserarwa) kuma Muka hallakar da maɓarnata.

10. Haƙiƙa Mun saukar muku da littafi (wanda) a cikinsa akwai ɗaukakarku; me ya sa ba kwa hankalta?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar da amsa ne ga maganar kafirai da suka yi ta cewa Allah ba zai aiko mutum ba, sai ya tabbatar musu da cewa bai taɓa aiko da wani manzo ba kafin Annabi (ﷺ) sai mutum namiji wanda ya riƙa yi masa wahayi. Allah bai aiko da mala'ika ba. Don haka ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa kafirai masu waccan magana cewa, su tambayi malaman Ma'abota Littafi za su faɗa masu gaskiyar labarin idan su ba su sani ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar musu da cewa babu wasu manzanni da ya aiko, kuma ya yi su jiki kawai ba sa cin abinci. Su ma suna cin abinci kamar kowa, kuma suna mutuwa idan lokacin mutuwarsu ya zo, ba masu wanzuwa ne ba har abada.
Sai kuma ya bayyana cewa ya aiko waɗannan manzanni zuwa ga al'ummunsu, wasu suka gaskata su, wasu kuma suka ƙaryata su, sai Allah ya cika wa manzannin nan da muminai alƙawarinsa ya kuɓutar da su daga hallaka, ya kuma hallakar da kafirai maɓarnata saboda kafircinsu da ƙetare iyakokinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jawo hankalinsu zuwa ga fahimtar darajar Alƙur'ani da ɗaukakarsa da cewa, ya saukar musu da Alƙur'ani wanda ya ƙunshi ɗaukakarsu kuma abin alfaharinsu, idan har sun yi imani da shi sun yi aiki da karantarwarsa. Yanzu bai kamata su gane hakan ba, su yi gaggawa wajen yin imani da shi da aiki da koyarwarsa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mummunan ƙarshen zalunci da azzalumai.

2. Jin daɗi da holewa yakan iya jawo faɗawa cikin zalunci da kauce wa hanyar Allah.

3. Nadama da da-na-sani ba su da wani amfani ga mai yin su bayan azabar Allah ta riga ta zo masa.

4. Idan azabar Allah ta riga ta zo to babu wurin gudu ko tsira.

Suratul Anbiya (11-15)
وَكَمۡ قَصَمۡنَا مِن قَرۡيَةٖ كَانَتۡ ظَالِمَةٗ وَأَنشَأۡنَا بَعۡدَهَا قَوۡمًا ءَاخَرِينَ ١١ فَلَمَّآ أَحَسُّواْ بَأۡسَنَآ إِذَا هُم مِّنۡهَا يَرۡكُضُونَ ١٢ لَا تَرۡكُضُواْ وَٱرۡجِعُوٓاْ إِلَىٰ مَآ
أُتۡرِفۡتُمۡ فِيهِ وَمَسَٰكِنِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تُسۡـَٔلُونَ ١٣ قَالُواْ يَٰوَيۡلَنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ١٤ فَمَا زَالَت تِّلۡكَ دَعۡوَىٰهُمۡ حَتَّىٰ جَعَلۡنَٰهُمۡ حَصِيدًا خَٰمِدِينَ ١٥

11. Al'ummu nawa ne kuma Muka hallakar (waɗanda) suka kasance azzulumai, Muka kuma halicci wasu mutanen daban bayansu?

12. Lokacin da suka fara jin azabarmu sai ga su suna guje mata.

13. (Aka ce da su): "Kada ku gudu, ku dawo zuwa ga abin da aka ni'imta ku da shi, da kuma gidajenku don a yi muku tambayoyi."

14. Suka ce: "Kaiconmu, lallai mu kam mun kasance azzalumai!"

15. Sannan waccan (maganar tasu) ba su daina faɗar ta ba har Muka mai da su girbabbu, matattu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya hallaka al'ummu da yawa saboda zaluncinsu da kafircinsu, ya kuma maye gurabensu da wasu al'ummun daban. Lokacin da azabar Allah ta zo wa waɗannan al'ummun suka gan ta ƙuru-ƙuru sai suka fice daga gidajensu da garuruwansu suna ƙoƙarin gudu wai su tsira da rayuwarsu. Sai aka riƙa kiran su cikin izgili da tsokana ana faɗa musu cewa su koma gidajensu da garuruwansu inda suka riƙa yin rayuwar tamore da bushasha domin a yi musu tambayoyi a kan rayuwarsu ta duniya. Hakan kuwa ba zai taɓa saɓuwa ba, domin azabar Allah ta riga ta zo musu babu mafaka ko maɓuya. Don haka ne azzalumai za su yi ta kururuwa da nadama marar amfani suna kiran ya kaiconsu, lallai su sun tabbata azzalumai saboda sun kafirce wa Allah da manzanninsa sun ƙi gaskiya. Allah ya bayyana cewa haka za su ci gaba da kururuwa suna surutai na nadama da kaico har sai ya mayar da su kamar girbabbiyar shuka matattu ko shurawa babu mai iya yi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halitta ba tare da wata hikima ba.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rushe ƙarya ne ta hanyar bayyana wa mutane gaskiya a bisa harshen manzanninsa, ya kuma ba wa mutane damar fahimtar gaskiyar yayin da suka ji ta, ta yadda za su iya bambance tsakanin gyara da ɓarna, ko kuma ya gwara kan maɓarnatan su riƙa rushe junansu da kansu.

3. Gaskiya idan ta zo nan da nan takan rushe ƙarya, domin tasirinta na gaggawa ne.

4. Babu wata jayayya ko ruɗani na nassi ko hankali da wani zai kawo don daƙile gaskiya ko kawar da ita face sai an samu ƙarfafan hujjojin Shari'a na nassi da na hankali sun yi rugu-rugu da wannan ruɗanin ya wargaje cikin sauƙi.

Suratul Anbiya (16-20)
وَمَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَآءَ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا لَٰعِبِينَ ١٦ لَوۡ أَرَدۡنَآ أَن نَّتَّخِذَ لَهۡوٗا لَّٱتَّخَذۡنَٰهُ مِن لَّدُنَّآ إِن كُنَّا فَٰعِلِينَ ١٧ بَلۡ نَقۡذِفُ بِٱلۡحَقِّ عَلَى ٱلۡبَٰطِلِ فَيَدۡمَغُهُۥ فَإِذَا هُوَ زَاهِقٞۚ وَلَكُمُ ٱلۡوَيۡلُ مِمَّا تَصِفُونَ ١٨ وَلَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَمَنۡ عِندَهُۥ لَا يَسۡتَكۡبِرُونَ عَنۡ عِبَادَتِهِۦ وَلَا يَسۡتَحۡسِرُونَ ١٩ يُسَبِّحُونَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ لَا يَفۡتُرُونَ ٢٠

16. Kuma ba Mu halicci sama da ƙasa da kuma abin da yake tsakaninsu don wasa ba.

17. In da Mun yi nufin Mu riƙi (abin) da zai shagaltar (mata ko ɗa), to da sai Mu riƙe shi daga waɗanda suke a wurinmu, idan har za Mu yi hakan.

18. A'a, ba haka ba ne, Muna jefa gaskiya a kan ƙarya, sai ta yi rugu-rugu da ita, sai (ka gan ta) ta ɓace ɓat. Kuma tsananin azaba ya tabbata a gare ku saboda abin da kuke siffanta (Shi da shi).

19. Duk kuwa waɗanda suke sammai da ƙasa nasa ne, kuma waɗanda suke wurinsa ba sa girman kai game da bauta masa, kuma ba sa gajiya.

20. Suna tasbihi dare da rana ba sa ƙosawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu dalilai na cikar ikonsa a kan komai da cancantar a bauta masa shi kaɗai. Da cewa bai halicci sama da ƙasa da abin da yake tsakaninsu don wasa

ba. Ya halicce su ne don nuna cikar ikonsa da Kudurarsa. Ya tabbatar da cewa da a ce yana nufin ya riƙi abin da zai shagaltar da shi kamar mata ko ɗa, to da sai ya riƙe shi daga waɗanda suke tare da shi, a can cikin sammai ba a ƙasa ba, domin girman darajar sama ɗin ne ma Allah ya halicci mafiya yawan masu bauta masa a cikinta. To amma Allah ba zai yi hakan ba, domin ya tsarkaka da a ce ya riƙi ɗa ko mata.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi ne ya ɗauki nauyin ruguza ƙarya a duk inda take, domin da zarar ya yi wa Manzonsa wahayi da gaskiya sai ya jefa wannan gaskiyar a kan ƙaryar kafirai sai ta yi daga-daga da ita, ta wargaje, ta gushe cikin gaggawa, a nemeta a rasa. Sannan Allah ya bayyana cewa tsananin azaba ya tabbata ga azzalumai masu cewa Allah yana da mata ko ɗa, domin wannan siffanta Allah ne da abin da sam bai kamace shi ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi ne mamallakin sammai da ƙasa, don haka shi ba mabuƙaci ne ga komai ba har da zai riƙi mata ko ɗa. Kowa da komai masu buƙata ne a wurinsa. Kuma mala'ikun da suke wajensa waɗanda wasu mushirikai suke cewa 'ya'yansa ne mata, to wannan shaci-faɗinsu ne; dukkansu bayinsa ne masu bautar sa dare da rana ba sa girman kai wajen bauta masa ba kuma sa gajiya da haka. Suna kuma tsarkake Allah dare da rana ba sa ƙosawa.

An karɓo daga Hakim ɗan Hizam (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Annabi (ﷺ) yana zaune tsakiyar sahabbansa sai ya ce musu: "Shin kuwa kuna jin abin da nake ji." Sai suka ce: "Babu abin da muke ji." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lallai ni ina jin ƙarar sama, kuma ba za a zarge ta ba idan ta yi ƙara, domin babu masaka tsinke a cikinta face akwai wani mala'ika a wurin, yana mai sujjada, ko a tsaye." [Ibn Abi Hatim, At-Tafsir 1072].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da Kaɗaitakar mulkin Allah a sammai da ƙasa saboda tabbatar gudanarsa a kan tsari guda ɗaya ba tare da saɓawa ba. Da a ce Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da abokan tarayya cikin mulkinsa masu ƙarfi da iko kamar nasa to da an samu jayayya a tsakaninsu wajen gudanar da tsarin sammai da ƙasa da sauran halittu. Da kuwa haka ta faru to da tsarin tafiyar da su gaba ɗaya ya wargaje. Rashin ganin hakan kuwa dalili ne a kan rashin samuwar abokin tarayya tare da Allah a sama ko a ƙasa.

2. Duk wanda ba Allah ba to abin yi wa hisabi ne da bincike a kan ayyukansa, domin shi bawan Allah ne, Allah ne kaɗai wanda babu wanda ya isa ya yi masa tambaya ta bincike da hisabi a kan aikinsa domin shi ne mamallakin kowa da komai.

3. Duk manzannin da Allah ya aiko sun zo ne da saƙon a bauta wa Allah shi kaɗai ba tare da shirka ba, kuma duk wani abin bauta ba Allah ba ƙarya ne.

Suratul Anbiya (21-25)
أَمِ ٱتَّخَذُوٓاْ ءَالِهَةً مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ هُمۡ يُنشِرُونَ ٢١ لَوۡ كَانَ فِيهِمَآ ءَالِهَةٌ إِلَّا ٱللَّهُ لَفَسَدَتَاۚ فَسُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ ٱلۡعَرۡشِ عَمَّا يَصِفُونَ ٢٢ لَا يُسۡـَٔلُ عَمَّا
يَفۡعَلُ وَهُمۡ يُسۡـَٔلُونَ ٢٣ أَمِ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةٗۖ قُلۡ هَاتُواْ بُرۡهَٰنَكُمۡۖ هَٰذَا ذِكۡرُ مَن مَّعِيَ وَذِكۡرُ مَن قَبۡلِيۚ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٱلۡحَقَّ
فَهُم مُّعۡرِضُونَ ٢٤ وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ٢٥

21. Shin ko sun riƙi wasu ababen bauta a nan ƙasa ne waɗanda suke raya matattu?

22. Da ya zamana akwai wasu ababen bauta ba Allah ba a cikinsu (wato sammai da ƙasa), to da sun lalace. Sai dai tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin Al'arshi game da abin da suke siffata (Shi da shi).

23. Ba a tambayar Sa game da abin da yake aikatawa, su dai ne za a tambaye su.

24. Ko kuma sun riƙi wasu ababen bauta ne ba Shi ba? Ka ce (da su): “To ku kawo dalilinku (a kan haka). Ga wa’azin waɗanda suke tare dani (watau Alƙur’ani), ga kuma wa’azin waɗanda suka gabace ni (watau littattafan annabawa sai ku duba).” A’a, yawancinsu dai ba sa sanin gaskiya sannan kuma masu bijire (mata) ne.

25. Kuma ba wani manzo da Muka aiko gabaninka face sai Mun yi masa wahayi cewa, babu wani abin bauta da gaskiya sai Ni; to sai ku bauta min.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya musanta wa mushirikai yadda suka rungumi wasu gumaka suna bauta musu ba Allah ba, kuma su da kansu sun tabbata da cewa waɗannan allolin ba za su iya tayar da matattu bayan mutuwarsu ba, to saboda me suke bautar wasu gajiyayyu marasa ikon komai?
Sai kuma ya bayyana dalili na hankali da yake tabbatar da cewa Allah Ɗaya ne ba shi da abokin tarayya, da cewa, da a ce akwai wasu alloli tare da Allah waɗanda su ma suke da iko irin nasa, suke iya aikata abin da suka ga dama, to da tuni tsarin gudanar da sammai da ƙasa ya lalace, sauran halittu ma sun lalace, domin za a sami jayayya tsakanin allolin masu cikakken iko iri guda. To amma wanzuwar sammai da ƙasa a kan tsari guda tutur shi yake tabbatar da Kaɗaitakar Allah. Don haka Allah ya tabbatar da cewa ya tsarkaka daga dukkan abin da suke siffanta shi da shi na yin tarayya da wasu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikakken mulkinsa a kan bayinsa, da cewa shi kaɗai ne mai aikata yadda ya ga dama, ya haramta abin da ya so, babu wanda ya isa ya yi masa tambaya a kan duk abin da ya aikata ko hukuncin da ya yanke ya zartar. Shi ne kuma yake da ikon tambayar bayinsa game da duk abin da suka aikata sannan ya yi musu sakayya a kai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kore wata hujja ta ilimi wadda masu haɗa shi da wasu wurin bauta suka dogara da ita da cewa suna bauta musu ne kawai ba tare da wani ilimi ba. Ya umarci Annabi (ﷺ) da ya nemi mushirikan da su kawo hujjojinsu masu nuna cancantar gumakansu ga bauta. Ya kuma bayyana musu cewa ga Alƙur’ani nan da aka saukar masa ga kuma littattafan da aka saukar wa sauran annabawa, a cikinsu duka babu wata hujja mai nuna a haɗa Allah da wasu ababe daban a wajen bauta. Don haka ya tabbatar da cewa yawancinsu ba su da wani ilimi da suke dogaro da shi sai ra’ayin riƙau da jahilici da kuma bijire wa gaskiya ba sa son sauraron ta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafa batun bauta masa shi kaɗai da cewa, babu wani manzo da ya aiko gabanin Manzon Allah (ﷺ) sai da ya yi masa wahayi cewa, babu wani abin bautawa da gaskiya sai shi kaɗai, don haka su bauta masa kada su haɗa shi da ƙowa wajen bauta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin muguwar aƙidar Larabawa masu cewa mala’iku mata ne kuma ‘ya’yan Allah.

2. Bayanin siffofin mala’ikun Allah da girman matsayinsu a wurinsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tun farko ya halicci mala’iku don su yi masa biyayya da zartar da umarninsa, don haka ne sabo ba zai taba bayyana daga gare su ba sam.

4. Babu mai ceto a gaban Allah sai wanda ya ba wa izinin ya yi ceto kuma ga wanda ya yarda a cece shi. Don haka ceto duka na Allah ne a wurinsa ake neman sa ba wurin wani ba.

5. Mala’iku duk matsayinsu da girmansu a wurin mahaliccinsu ba su isa a bauta musu ba, to ina ga wani mahaluƙi wanda bai kai darajarsu da matsayinsu ba?

Suratul Anbiya (26-29)

وَقَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱلرَّحۡمَٰنُ وَلَدٗاۗ سُبۡحَٰنَهُۥۚ بَلۡ عِبَادٞ مُّكۡرَمُونَ٢٦ لَا يَسۡبِقُونَهُۥ بِٱلۡقَوۡلِ وَهُم بِأَمۡرِهِۦ يَعۡمَلُونَ٢٧ يَعۡلَمُ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡ وَلَا يَشۡفَعُونَ إِلَّا لِمَنِ ٱرۡتَضَىٰ وَهُم مِّنۡ خَشۡيَتِهِۦ مُشۡفِقُونَ٢٨ *وَمَن يَقُلۡ مِنۡهُمۡ إِنِّيٓ إِلَٰهٞ مِّن دُونِهِۦ فَذَٰلِكَ نَجۡزِيهِ جَهَنَّمَۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلظَّٰلِمِينَ٢٩

26. Suka kuma ce wai Allah Ya riƙi ɗa (daga cikin mala’iku)! Tsarki ya tabbata a gare Shi. A’a, su bayi dai ne ababen girmamawa.

27. Ba sa rigayar Sa da magana, su kuma da umarninsa suke aiki.

28. Yana sane da ayyukansu da suka gabatar da na nan gaba, ba kuma za su yi ceto ba sai ga wanda Ya yarda (daga bayinsa), suna kuwa masu kaffa-kaffa don tsoron Sa.

29. Daga cikinsu kuwa duk wanda ya ce: “Ni abin bauta ne ba shi (Allah) ba,” to wannan za Mu saka masa da (wutar) Jahannama. Kamar haka kuwa Muke saka wa azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana cikakkun dalilai masu nuna tsarkakarsa daga duk wani abokin tarayya, da kuma rusa aƙidar mushirikan Larabawa masu cewa wai mala’iku ‘ya’yan Allah ne mata. Allah ya tsarkake kansa daga wannan mummunan furuci nasu, ya tabbatar musu da cewa mala’iku bayin Allah ne masu girma da daraja a wurinsa amma ba ‘ya’yansa ba.
Ya kuma bayyana irin biyayyarsu da ladabinsu gare shi; ba sa rigayar sa da wata magana sai ya umarce su da su faɗi wani abu, sannan kuma idan ya umarce su da aikata wani abu to ba sa saɓa umarninsa ko kaɗan suna bin sa sau da ƙafa.
Ya kuma bayyana yadda iliminsa ya kewaye komai nasu ya san duk ayyukansu na baya da waɗanda za su yi a nan gaba, don haka duk abin da suke yi da saninsa suke yin sa. Wannan ya sanya ko da ceto a ranar alƙiyama ba za su yi wa kowa ba sai da izininsa kuma ga wanda ya yarda a ceta, sannan kuma koyaushe suna cike da tsoronsa, don haka ba za su taɓa saɓa ma umarninsa ko haninsa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa, da a ce wani mala’ika zai yi da’awar allanta, watau ya ce shi ma alla ne a bauta masa, to da lallai Allah ya yi masa mummunar azaba a wutar Jahannama, ya dawwama a cikinta har abada. Allah ya bayyana cewa wannan shi ne irin sakamakon da yake yi wa azzalumai masu kafirci da haɗa shi da abokan tarayya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara halittar sammai da ƙasa a manne da juna ne sannan daga bisani ya raba tsakaninsu.

2. Ruwa shi ne jigon rayuwar duk wani abu mai rai.

3. Rana da wata masu tafiya ne kowanne a cikin falaƙinsa.

Suratul Anbiya (30-33)

أَوَ لَمۡ يَرَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَنَّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ كَانَتَا رَتۡقٗا فَفَتَقۡنَٰهُمَاۖ وَجَعَلۡنَا مِنَ ٱلۡمَآءِ كُلَّ شَيۡءٍ حَيٍّۚ أَفَلَا يُؤۡمِنُونَ ٣٠ وَجَعَلۡنَا فِي ٱلۡأَرۡضِ رَوَٰسِيَ أَن تَمِيدَ بِهِمۡ وَجَعَلۡنَا فِيهَا فِجَاجٗا سُبُلٗا لَّعَلَّهُمۡ يَهۡتَدُونَ ٣١ وَجَعَلۡنَا ٱلسَّمَآءَ سَقۡفٗا مَّحۡفُوظٗاۖ وَهُمۡ عَنۡ ءَايَٰتِهَا مُعۡرِضُونَ ٣٢ وَهُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ وَٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ كُلّٞ فِي فَلَكٖ يَسۡبَحُونَ ٣٣

30. Yanzu waɗanda suka kafirta ba sa ganin cewa a da can sammai da ƙasa a haɗe suke, sannan Muka raba su; Muka kuma halicci duk wani abu mai rai daga ruwa? To me ya sa ba za su yi imani ba?

31. Muka kuma sanya kafaffun duwatsu a ƙasa don kar ta yi tangal-tangal da su, Muka kuma sanya wuraren tafiya a cikinta (su zama) hanyoyi don su gane (inda za su).

32. Muka kuma sanya sama (ta zama) rufi tsararre; su kuwa (duk da haka) masu bijire wa ayoyinta (watau sama) ne.

33. Shi ne kuma Wanda Ya halicci dare da rana, da kuma rana da wata; kowannensu yana ninƙaya cikin falakinsa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin kafirai a kan su yi duba zuwa ga dalilai masu tabbatar da cikar Kudurarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai, da cewa yanzu su kafirai ba su san cewa a da sama da ƙasa a manne suke ba sai Allah ya raba su, ya sanya girgije a sama mai zubo da ruwa ya kuma fitar da tsirrai daga cikin ƙasa? Wannan ruwan ne kuma ya mayar da shi madogara ga duk wani abu mai rai, mutum da dabba da sauran halittu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ce: “Ya Manzon Allah, lallai ni duk sanda na gan ka sai in ji daɗi, farin ciki ya lulluɓe ni, ka ba ni labari game da komai.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Komai an halicce shi daga ruwa ne.” [Ahmad #7932].

Allah ya bayyana cewa, yanzu wannan kaɗai bai isa ya sa kafirai su yi imani da Allah ba su bauta masa shi kaɗai?
Sai kuma ya ci gaba da lissafa wasu ƙarfafan dalilai game da sama, daga cikinsu akwai duwatsu waɗanda ya kafa su a matsayin turaku waɗanda suke riƙe da ƙasa don kada ta riƙa tangal-tangal da halittun kan doronta. Ya kuma tanadar wa matafiya hanyoyi a bayanta waɗanda suke bi don kai-komonsu da tafiye-tafiyensu. Ya kuma bayyana cewa ya sanya sama ta zama wani amintaccen rufi da ba a tsoron ya faɗo, ga shi kuwa ba ya da wani ginshiƙi da ke riƙe da shi. Kuma ya saka tsaro mai tsanani a cikin sararin samaniya saboda hana shaiɗanu satar sauraro. To amma duk da waɗannan ayoyi da dalilai da Allah yake nuna wa mushirikai sun ci gaba da bijire wa ayoyin nan na samaniya, kamar rana da wata da taurari, ba sa ɗaukar wata izina daga gare su ballantana har su yi imani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da cewa shi ne wanda ya halicci dare domin ya zama lokacin hutawa, ya kuma halicci yini domin ya zamanto lokacin fita neman abinci, ya kuma halicci rana don ta zama alama ce ta yini, wata kuma don ya zamanto shi ne alamar dare, sannan kowannensu ya fitar masa da hanyarsa, watau falakinsa wanda yake gudu a cikinsa ba tare da kaucewa ko kuskurewa ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani mai rai mamaci ne.

2. Duk abin da Allah ya bai wa bawa mai daɗi ko marar daɗi, na alheri ko na sharri, to jarraba ce don ya bayyana wanda ya fi kyautata aikinsa daga cikin bayinsa. Don haka jarraba ba ta taƙaita a kan mummunan abu ba kaɗai.

3. Har kullum kafirai suna sukan muminai da abin da yake shi ne abin yabo a tare da su, kamar tsantsanta ibada ga Allah da sukan duk wani abu da ake bauta wa ba Allah ba da bayanin matsayinsa. Wannan shi ne kamala kuma shi ne abin yabo. Kafirai su ne suka cancanci suka da izgili domin su ne suka siffantu da duk wata mummunar siffa abar kushewa. Babu wata mummunar siffar da ta kai kafirce wa Allah da Manzonsa da maganarsa.

4. Kafiri ya tabbata babban butulu domin Allah mahaliccinsa yake yi wa butulci duk da ni'imomin da ya baibaye shi da su.

Suratul Anbiya (34-36)

وَمَا جَعَلۡنَا لِبَشَرٖ مِّن قَبۡلِكَ ٱلۡخُلۡدَۖ أَفَإِيْن مِّتَّ فَهُمُ ٱلۡخَٰلِدُونَ ٣٤ كُلُّ نَفۡسٖ ذَآئِقَةُ ٱلۡمَوۡتِۗ وَنَبۡلُوكُم بِٱلشَّرِّ وَٱلۡخَيۡرِ فِتۡنَةٗۖ وَإِلَيۡنَا تُرۡجَعُونَ ٣٥ وَإِذَا رَءَاكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِن يَتَّخِذُونَكَ إِلَّا هُزُوًا أَهَٰذَا ٱلَّذِي يَذۡكُرُ ءَالِهَتَكُمۡ وَهُم بِذِكۡرِ ٱلرَّحۡمَٰنِ هُمۡ كَٰفِرُونَ ٣٦

34. Ba Mu kuma sanya wa wani mutum dawwama ba a gabaninka; to yanzu idan ka mutu su ɗin masu dawwama ne?

35. Kowanne rai zai ɗanɗani mutuwa. Muna kuwa jarrabar ku da fitinar sharri da ta alheri, kuma gare Mu ne za a dawo da ku.

36. Idan kuma waɗanda suka kafirta su ka gan ka, ba abin da suke yi maka sai izgili (suna cewa): "Yanzu wannan shi ne wanda yake aibata allolinku?" Alhali kuwa su suna kafirce wa ambaton (Allah) Mai rahama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a gabanin zuwan Manzon Allah (ﷺ) babu wani ɗan'adam da ya dawwama a bayan ƙasa, don haka fatan mutuwa da mushirikai suke yi wa Manzon Allah (ﷺ) aikin banza ne, ba shi da wani tasiri, don ko ba su yi masa fatan ya mutu ba da man ai zai mutu, yayin da ajalinsa ya zo kwanakinsa na duniya suka ƙare, kamar yadda annabawa da manzannin farko suka rayu kuma suka mutu. Sannan kuma idan Annabi (ﷺ) ya mutu kamar yadda suke jira, shin su za su dawwama ne a raye ba za su mutu ba?
Sai kuma ya tabbatar da cewa mutuwa riga ce da kowa sai ya sanya ta a wuyansa; duk wani mahaluƙi sai ya ɗanɗani mutuwa komai daɗewa, sai dai kawai bayi su sani cewa Allah ya yiwo su a duniya, ya umarce su ya kuma hana su; ya jarrabe su da alheri kamar wadata, da kuma sharri kamar talauci, don ya tantance na ƙwarai da wanda ba na ƙwarai ba daga cikinsu. Sannan bayan kowa ya mutu za a koma gaba ɗaya ne zuwa ga Allah don ya yi wa kowa sakamako a kan ayyukansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halayyar kafirai lokacin da suka ga Annabi (ﷺ) yana wa'azi, sai su riƙa yi masa izgili suna nuna shi suna cewa, yanzu wannan ne yake zagin iyayen gijinsu da suke bauta wa? Suna yin wannan izgili tare da kafirce wa Alƙur'ani da Allah ya saukar da kuma butulce wa ni'imomin da ya ba su na rayuwa. Don haka su ne suka fi cancantar a kushe musu ba Manzon Allah ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin kafircin wanda yake yi wa Manzon Allah (ﷺ) izgili da magana ne ko da aiki.

2. Duk wanda yake yi wa Manzon Allah (ﷺ) izgili to wannan ya halaka, ƙarshensa ba zai yi kyau ba.

3. Yana daga ɗabi'ar ɗan'adam ya zama mai son gaggawa. Bin abu a sannu a hankali halayya ce mai kyau.

Suratul Anbiya (37-41)
خُلِقَ ٱلۡإِنسَٰنُ مِنۡ عَجَلٍۚ سَأُوْرِيكُمۡ ءَايَٰتِي فَلَا تَسۡتَعۡجِلُونِ ٣٧ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٣٨ لَوۡ يَعۡلَمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ حِينَ لَا يَكُفُّونَ عَن وُجُوهِهِمُ ٱلنَّارَ وَلَا عَن ظُهُورِهِمۡ وَلَا هُمۡ يُنصَرُونَ ٣٩ بَلۡ تَأۡتِيهِم بَغۡتَةٗ فَتَبۡهَتُهُمۡ فَلَا يَسۡتَطِيعُونَ رَدَّهَا وَلَا هُمۡ يُنظَرُونَ ٤٠ وَلَقَدِ ٱسۡتُهۡزِئَ بِرُسُلٖ مِّن قَبۡلِكَ فَحَاقَ بِٱلَّذِينَ سَخِرُواْ مِنۡهُم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٤١

37. An halicci mutum da son gaggawa. Ba da daɗewa ba zan nuna muku ayoyina, to don haka kada ku nemi gaggauto da (zuwansu).

38. Suna kuma cewa: "Wai yaushe ne wannan alƙawarin (na alƙiyama zai zo) idan kun kasance masu gaskiya?"

39. Da waɗanda suka kafirta za su san lokacin da za su kasa kare fuskokinsu daga wuta, da kuma bayansu, ba kuma za a taimake su ba (to da ba su faɗi haka ba).

40. A'a, za ta zo musu ne ta farat- ɗaya sai ta rikirkita su, ba kuwa za su iya kawar da ita ba, kuma su ba za a saurara musu ba.

41. Haƙiƙa kuma an yi izgili ga manzannin da suka gabace ka, sai sakamakon abin da suke yin izgili da shi ya aukar wa masu yin izgilin.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ɗabi'ar jinsin ɗan'adam ta garaje da rashin bin abu a sannu. Wannan ɗabi'ar ce ta sanya kafirai suka riƙa gaggauto da aukuwar azaba a kansu wai idan har Manzon Allah mai gaskiya ne. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, ba jimawa zai nuna musu azabar tasa wadda suke gaggauto zuwanta, don haka ba ma sai sun nemi gaggauto ta ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai suna ƙaryata ranar alƙiyama har ma suna tambayar muminai cewa in da gaske ne za ta zo to yaushe ne za ta zo idan har muminai gaskiya suke faɗa? A nan ma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar wa kafirai martani da cewa, da a ce sun san lokacin da za su kasa kare fuskokinsu da bayansu daga wuta, kuma ba za su sami mai taimakon su ba wanda zai kare musu azabar, to da ba su riƙa neman a gaggauto da zuwan wannan ranar ba.
Sai ya bayyana musu cewa wannan wutar da za a yi musu azaba da ita a wannan ranar ba za su san lokacin zuwanta ba, sai dai ta zo musu kwatsam ba zato ba tsammani, duk ta rikirkita su da tsoro da fargaba, ba kuma za su iya kare kansu daga gare ta ba, kuma ba za a jinkirta musu ba ballantana har su sami damar su tuba Allah ya yi musu rahama. Watau da kafirai masu ja da ranar alƙiyama sun sakankance da wannan rana da ba su gaggauto da azaba ba, da sun kasance cike da tsoro da fargaba a koyaushe, to amma da yake ba su san haka ba shi ne suke irin wannan cika baki.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci abin da Manzon Allah (ﷺ) ya sha fama da shi na izgilin mutanensa gare shi da ƙaryata shi. Allah ya lallashe shi a kan haka, da cewa ba shi kaɗai ne manzon da mutanensa suka yi masa izgili ba; an yi wa manzanni da dama a gabaninsa izgili, to amma daga ƙarshe sai

azabar da suke yin izgili game da ita ta auka musu, ta kewaye su ta ko'ina, Allah ya hallaka su gaba ɗayansu. Don haka su ma masu yi wa Manzon Allah izgili su shiga taitayinsu kada irin abin da ya sami waɗancan su ma ya same su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu mai ba da kariya daga azabar Allah sai Allah shi kaɗai.

2. A koyaushe ɗan'adam yana ƙarkashin tsaron Ubangiji ne. Wannan ɗaya ce daga cikin ɗimbin ni'imominsa ga bayinsa, amma da yawa ba su san haka ba.

3. Duk wanda ya yi nesa da ambaton Allah da sauraron wa'azinsa, to ba zai taɓa juyowa ya bar ɓatan da yake kai ba.

4. Daɗewar kafirai a cikin ni'imar Allah ta rayuwar duniya ita ce ta ƙara musu zaƙewa a cikin kafircinsu da shirkarsu, har ta kai suna ganin su a kan gaskiya suke, muminai a kan ɓata.

5. Tsayawa da yin tunani game da rayuwar al'ummun da suka shuɗe da yadda Allah ya yi da su yana ƙara wa bawa tsoron Allah da gyara halinsa da guje wa saɓon Allah.

6. Karya ba ta ɗorewa komai daɗewarta kuwa. Gaskiya ita ce mai wanzuwa har abada.

Suratul Anbiya (42-44)
قُلۡ مَن يَكۡلَؤُكُم بِٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ مِنَ ٱلرَّحۡمَٰنِۚ بَلۡ هُمۡ عَن ذِكۡرِ رَبِّهِم مُّعۡرِضُونَ ٤٢ أَمۡ لَهُمۡ ءَالِهَةٞ تَمۡنَعُهُم مِّن دُونِنَاۚ لَا يَسۡتَطِيعُونَ نَصۡرَ أَنفُسِهِمۡ وَلَا هُم مِّنَّا يُصۡحَبُونَ ٤٣ بَلۡ مَتَّعۡنَا هَٰٓؤُلَآءِ وَءَابَآءَهُمۡ حَتَّىٰ طَالَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡعُمُرُۗ أَفَلَا يَرَوۡنَ أَنَّا نَأۡتِي ٱلۡأَرۡضَ نَنقُصُهَا مِنۡ أَطۡرَافِهَآۚ أَفَهُمُ ٱلۡغَٰلِبُونَ ٤٤

42. Ka ce (da su): "Wane ne yake kare ku dare da rana daga (azabar Allah) Mai rahama?" A'a su dai masu bijire wa ambaton Ubangijinsu ne.

43. Ko kuwa suna da ababen bauta ne da za su kare su (daga azaba) ba Mu ba? Ba za su iya taimakon kansu ba, kuma ba za a kiyaye su (daga azabarmu) ba.

44. A'a, Mun dai jiyar da waɗannan daɗi ne su da iyayensu, har dai rayuwa ta tsawaita a gare su. Yanzu ba sa ganin cewa Mu Muna zo wa ƙasa Muna cinye iyakokinta da kaɗan-kaɗan? Yanzu su ne masu yin rinjaye?.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana gazawar allolin da kafirai suke haƙilon bauta wa. Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya tambaye su cewa, wane ne zai iya ba su kariya da daddare lokacin da suke cikin gidajensu suna barci, ko da rana lokacin da suka fita hadahadarsu idan Allah mai rahama ya nufi saukar musu da azabar da za ta hallaka su? Tabbas ba su da wasu masu ba su tsaro in ba Allah ba, to amma duk da haka suna bijire wa wa'azozin Ubangijinsu da hujjojin da yake bayyana musu a koyaushe ba sa ɗaukar wa'azi ko izina daga gare su.
Sai Allah ya sake tambayar su cewa, shin ko suna da wasu alloli ne da suke bauta wa waɗanda za su kare su daga azabar Allah idan ya yi nufin saukar musu da ita? Allah ya tabbatar musu da cewa su allolin nasu ba za su ma iya taimakon kawunansu ba, su hana wani mummunan abu ya same su, ko su jawo wa kawunansu wani abu mai amfani. To wanda bai amfani kansa ba, bai taimaki kansa ba ta yaya zai amfani

wani ko ya taimaka masa?! Ga shi kuma ba waɗanda za su sami kariya ne ba daga Allah idan azabarsa ta zo.
Sai kuma ya bayyana dalilin da ya sa kafirai suke ci gaba da kafircinsu yadda suke so, watau ganin yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su jin daɗin rayuwa ya hore musu ni'imominsa su da iyayensu, suna ta wadaƙarsu yadda suke so, ba su san cewa talala ce Allah yake yi musu ba. Suka daɗe cikin rayuwar jin daɗi da morewa har wannan ya ruɗe su suka ci gaba da zama a kan kafircinsu, zukatansu suka ƙeƙashe, amma ba sa la'akari da yadda Allah yake ta tafiyar da rayuwar waɗansu. Wasu ma a gabaninsu ya hallaka su. Ko kuma ba su ga yadda ya riƙa tauye ƙasa ba kaɗan da kaɗan, mutanen cikinta suna ta raguwa saboda mutuwa? Yanzu wannan bai ishe su darasi ba, su ma su ji tsoron aukuwar irin haka gare su? Ko kuma suna tsammanin su sun gagara ne ba za a fi ƙarfinsu ba? Ko kusa! Tabbas za a fi ƙarfinsu, domin ba za su iya guje wa ikon Allah ba ko su hana mutuwa ta riske su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karfin hujjar mai kira zuwa ga Allah shi ne riƙo da Alƙur'ani da kafa hujja da shi.

2. Kafiri ba ya sauraron littafin Allah, ba ya amfanuwa da shi, domin ya kurumce daga sauraron sa. Mumini shi ne yake sauraron sa har ya amfana da shi.

3. Kurma shi ne wanda na'urar kunnuwansa ta sauraro ta lalace, don haka ko da akwai sauti ba zai ji ba domin lalacewar muhallin jin sautin a tare da shi. To hakanan wahayi shi ne yake raya zukata yake sawa a fahimci addinin Allah, to amma idan zuciyar da za ta fahimta ta lalace ba za ta karɓi gaskiyar ba ko shiriya ta shige ta kamar yadda sauti ba zai shiga kunnuwan kurma ba.

4. Don bawa ya amsa laifinsa wannan ba zai yi masa amfani ba idan har ya bari lokacin yin hakan ya riga ya wuce.

5. Tabbatar wa da Allah cikakken adalci da kore masa zalunci.6. Tabbatar da samuwar ma'aunan ayyukan bayi ranar alƙiyama.

Suratul Anbiya (45-47)
قُلۡ إِنَّمَآ أُنذِرُكُم بِٱلۡوَحۡيِۚ وَلَا يَسۡمَعُ ٱلصُّمُّ ٱلدُّعَآءَ إِذَا مَا يُنذَرُونَ ٤٥ وَلَئِن مَّسَّتۡهُمۡ نَفۡحَةٞ مِّنۡ عَذَابِ رَبِّكَ لَيَقُولُنَّ يَٰوَيۡلَنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ٤٦
وَنَضَعُ ٱلۡمَوَٰزِينَ ٱلۡقِسۡطَ لِيَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ فَلَا تُظۡلَمُ نَفۡسٞ شَيۡـٔٗاۖ وَإِن كَانَ مِثۡقَالَ حَبَّةٖ مِّنۡ خَرۡدَلٍ أَتَيۡنَا بِهَاۗ وَكَفَىٰ بِنَا حَٰسِبِينَ ٤٧

45. Ka ce (da su): "Ni kawai ina yi muku gargaɗi ne da wahayi." Kurame kuwa ba za su ji kira ba idan ma ana gargaɗin su.

46. Wallahi da wani ɗan furji na azabar Ubangijinka ya shafe su da tabbas za su ce: "Kaiconmu, lalle mu mun tabbata azzalumai."

47. Za Mu kuma sanya ma'aunai na adalci a ranar alƙiyama, sannan ba za a zalunci kowanne rai da komai ba, ko da ya zama gwargwadon ƙwayar komayya ne, za Mu zo da shi. Kuma Mun isa Masu hisabi!

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa kafirai cewa shi Manzo ne kawai daga Allah wanda ya zo yana gargaɗin su da wahayin da Ubangijinsa ya yi masa. To amma

sanannen abu ne cewa waɗanda kunnuwansu suka doɗe suka zamo kamar kurame ba sa ma sauraron kira da gargaɗin da ake yi musu, balle ya amfane su.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa, waɗannan kafiran masu gaggauto da azabar Allah a kansu, da a ce wani ɓangare na azabar zai ɗan shafe su, to da sun fara yin nadama suna kururuwar lallai sun hallaka sun yi hasara, kuma a lokacin za su tabbatar da cewa lallai sun zalunci kansu saboda sun haɗa Allah da wasu wajen bauta, sun ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da wahayin da ya zo musu da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikakken adalcinsa a ranar alƙiyama, da cewa a wannan ranar zai tattara halittun farko da na ƙarshe wuri guda, zai ajiye ma'aunan ayyuka na adalci domin auna ayyukan bayinsa. To babu wani rai da za a zalunce shi a ranar ta hanyar a rage masa kyawawan ayyukansa, ko a ƙara masa laifukan da bai aikata ba. Allah ya tabbatar da cewa a ranar za a yi awo na ƙeƙe-da-ƙeƙe, komai ƙanƙantar aiki ko da bai kai ƙwayar komayya ba, to sai an kawo shi an auna shi a wannan ma'auni na adalci. Allah ya tabbatar da cewa lallai shi ya isa mai hisabi da zai ƙalailaice ayyukan bayinsa gaba ɗaya.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wasu kalmomi biyu marasa nauyi a kan harshe, masu nauyi a kan ma'auni, ababen soyuwa ga Allah mai rahama su ne: *Subhanallahi wa bi hamdihi subhanallahil azim*." [Bukhari #6406 da Muslim #2694].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru ɗan Asi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah mai girma da buwaya zai waro wani mutum daga cikin al'umma a gaban sauran halittu, sai a buɗe masa kundin takardun ayyukansa guda casa'in da tara, kowane kundi iya ganin mutum, sai Allah ya ce masa: "A nan akwai abin da ba ka san da shi ba? Shin mala'ikun da suke kulawa da kai suna rubuta ayyukanka sun zalunce ka?" Sai ya ce: "A'a ya Ubangijina." Sai Allah ya ce masa: "To kana da wani hanzari ne ko wani kyakkyawan aiki?" Sai wannan mutum ya ruɗe ya kasa magana, sai kuma ya ce: "A'a ya Ubangijina." Sai Allah ya ce: "E, kana da wani kyakkyawan aiki guda ɗaya, a yau ba za a zalunce ka ba." Sai a fito masa da wani kati a cikinsa an rubuta *Ash-hadu an la ilaha illallahu wa ashhadu anna Muhammadan abduhu wa rasuluhu*." Sai Allah ya ce: "Ku kawo shi." Sai wannan mutum ya ce: "Ya Ubangijina, me wannan kati zai amfanar tare da waɗannan kundaye?" Sai a ce masa: "Lallai fa kai ba za a zalunce ka ba." Sai a ɗora waɗannan kundaye a cikin tafin ma'auni guda ɗaya, sai kawai su yi sakayau, wannan kati kuwa sai ya yi nauyi. Babu abin da zai nauyayi sunan Allah mai rahama mai jin ƙai." [Ahmad #6994 da Tirmizi #2639 da Ibn Majah #4300].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sau tari Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana haɗa ambaton Attaura da Alƙur'ani a wuri ɗaya, saboda zamantowarsu mafi girman littattafai da Allah ya saukar.

2. Littattafan da aka saukar su ne masu bambace tsakanin ƙarya da gaskiya, su ne haske mai kawar da duhu. Watsar da karantarwar manzannin Allah yana nufin taɓarɓarewar al'amura da rashin gane alƙibla da fagamniya a cikin duhun ɓata da jahilci da bidi'o'i.

3. Masu taƙawa su kaɗai ne suke amfanuwa da littafin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Alƙur'ani littafi ne wanda albarkarsa ta game ko'ina da ina. Yana daga cikin albarkarsa yadda ya ƙunshi bayanai filla-filla a kan sunayen Allah da siffofinsa da ayyukansa da siffofin manzanninsa da masoyansa, da bayanin hukunce-hukuncensa na ibada da mu'amaloli da bayanin lahira da makomar halittun Allah. Don haka wajibi ne ga masu son su sami albarkar rayuwa da haɓakarta duniya da lahira, su yi riƙo da shi su kuma yi aiki da shi.

Suratul Anbiya (48-50)

وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ٱلۡفُرۡقَانَ وَضِيَآءٗ وَذِكۡرٗا لِّلۡمُتَّقِينَ ٤٨ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُم بِٱلۡغَيۡبِ وَهُم مِّنَ ٱلسَّاعَةِ مُشۡفِقُونَ ٤٩ وَهَٰذَا ذِكۡرٞ مُّبَارَكٌ أَنزَلۡنَٰهُۚ أَفَأَنتُمۡ لَهُۥ مُنكِرُونَ ٥٠

48. Haƙiƙa Mun ba wa Musa da Haruna (Attaura) mai rarrabewa (tsakanin ƙarya da gaskiya) da kuma haske da shiriya ga masu taƙawa.

49. (Su ne) waɗanda suke tsoron Ubangijinsu ba tare da sun gan Shi ba, kuma su suna masu fargaba game da tashin alƙiyama.

50. Wannan (Alƙur'ani) kuwa tunatarwa ne mai albarka da Muka saukar da shi. Shin ku yanzu kwa riƙa musun sa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da littafinsa Attaura kamar yadda ya saba ambaton su, tare da ambaton Annabi Muhammadu (ﷺ) da littafin Alƙur'ani. Allah ya ba wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) littafin Attaura mai rarrabewa tsakanin gaskiya da ƙarya da tsakanin halal da haram, kuma haske mai shiryarwa ga muminai, mai tunatarwa ga masu taƙawa masu kiyaye dokokin Ubangijinsu.
Sai kuma ya bayyana ko su wane ne masu taƙawa, da cewa su ne waɗanda suke jin tsoron Ubangijinsu duk kuwa da ba sa ganin sa da idanuwansu, sannan koyaushe suna tsorace da ranar alƙiyama. Saboda cikakken saninsu ga mahaliccinsu Allah sai suka haɗa tsakanin ihsani da tsoro.
Sai kuma ya ambaci falalar Alƙur'ani da amfaninsa a rayuwar muminai, ya tabbatar da cewa shi tunatarwa ce ga dukkan abin da bawa zai so ya sani game da Allah da hukunce-hukuncen addininsa. Kuma mai albarka ne domin ya ƙunshi duk wani alheri na duniya da lahira. To amma duk da wannan matsayi nasa kafirai ba su yarda sun yi imani da shi ba, domin taɓewa da hasara.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabi Ibrahimu shiriyar da bai ba wa wani irinta ba in ban da Annabi Muhammadu (ﷺ), don haka ya zaɓe shi a matsayin badaɗayinsa.

2. Aikin wani in ba annabi ne ba ba ya zama hujja a addini.

3. Ba ya halatta a bi iyaye a cikin sha'anin addini a makance ba tare da dalilin Shari'a ba.

4. Wajen ƙoƙarin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) na yi wa mutanensa bayanin Tauhidi da haɗarin shirka ya kawo musu dalili na hankali da kuma dalili na nassi. Dalilin hankali a nan shi ne, ƙowa ya san cewa Allah ne shi kaɗai ya halicci sammai da ƙasa da mutum da aljan da dabbobi da sauran halittu gaba ɗaya, kuma shi ne mai mulkin su, shi yake gudanar da su gaba ɗaya. Daga cikin abubuwan da ya halitta har da gumakan da suke bauta wa ba shi ba. To ta yaya za su bar bautar wanda suka yarda shi ne mahaliccin komai su koma ga bautar wanda ba ya iya tsinana wa kansa komai ballantana har ya amfanar da mai bautar sa? Dalili na nassi kuwa shi ne shaidar shi kansa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda Allah ya zaɓe shi ya ba shi annabata, ya saukar masa da wahayinsa. Ya shaida ya kuma tabbatar da cewa Allah ne kaɗai ya cancanci bauta ba wani ba.

Suratul Anbiya (51-56)

*وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَآ إِبۡرَٰهِيمَ رُشۡدَهُۥ مِن قَبۡلُ وَكُنَّا بِهِۦ عَٰلِمِينَ ٥١ إِذۡ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوۡمِهِۦ مَا هَٰذِهِ ٱلتَّمَاثِيلُ ٱلَّتِيٓ أَنتُمۡ لَهَا عَٰكِفُونَ ٥٢ قَالُواْ وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا لَهَا عَٰبِدِينَ ٥٣ قَالَ لَقَدۡ كُنتُمۡ أَنتُمۡ وَءَابَآؤُكُمۡ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٥٤ قَالُوٓاْ أَجِئۡتَنَا بِٱلۡحَقِّ أَمۡ أَنتَ مِنَ ٱللَّٰعِبِينَ ٥٥ قَالَ بَل رَّبُّكُمۡ رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ ٱلَّذِي فَطَرَهُنَّ وَأَنَا۠ عَلَىٰ ذَٰلِكُم مِّنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ٥٦

51. Haƙiƙa kuma Mun bai wa Ibrahimu shiriyarsa tun da farko, Mun kuma zamanto Muna sane da shi.

52. (Ka tuna) lokacin da ya ce da babansa da kuma jama’arsa: “Mene ne (amfanin) waɗannan gumakan da kuka duƙufa a bautar su?”

53. Suka ce: “Mun sami iyayenmu suna bauta musu ne.”

54. (Ibrahimu) ya ce: “Haƙiƙa ku da iyayen naku kun tabbata a kan ɓata bayyananne.”

55. Suka ce: “Yanzu ka zo mana da gaskiya ne ko kuwa kai ma kana cikin masu wasa (da mu) ne?”

56. (Ibrahimu) ya ce: “A’a, Ubangijinku dai (Shi ne) Ubangijin sammai da ƙasa, Wanda Ya halicce su, kuma ni ina daga masu shaida a kan wannan.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa tun gabanin ya ba wa Annabi Musa da Haruna Attaura ya riga ya ba wa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ilimin sanin hujja mai ƙarfi tun yana ƙaraminsa, domin yana sane da shi da cancantarsa da annabta da zaɓin Ubangiji.
Allah ya bayyana yadda Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fara fuskantar mutanensa masu bautar gumaka da wa’azi da jan hankali, yayin da ya tambayi mahaifinsa Azara da mutanensa, game da waɗannan gumakan da suka duƙufa suna bautar su, alhalin ba wani amfani da suke samu a wurinsu? Sai suka amsa masa da cewa su dai sun tashi sun tarar iyayensu suna bauta musu ne don haka su ma suke aikata abin da iyayensu suka aikata. Watau dai wannan ita ce kawai hujjarsu ta bautar gumaka ba tare da wani ilimi ɗaga Allah ba.
Sai Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tabbatar musu cewa wannan karkatacciyar hanya da suke kai su da iyayensu ɓata ne bayyananne, domin shirka ce da Allah da barin ɗayanta Allah.
Sai wannan amsa ta Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ta ba su mamaki ta kuma ɗaure musu kai, sai suke tambayar sa: Wai shin da gaske yake yi kuwa ko kuma yana yi musu wasa ne da zolaya?
Sai ya mayar musu da martani cewa, tabbas shi fa da gaske yake, ya ma ƙara tabbatar musu da cewa Ubangijinsu shi ne Ubangijin sammai da ƙasa wanda ya ƙirƙiri halittarsu ba tare da ya kwaikwaya daga wurin wani ba, kuma shi tuni ya shaida da haka ya yi imani da Kaɗaitakar mahaliccinsa, bai yarda da gumakan da suke bauta wa ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cikar yaƙinin Annabi Ibrahimu da yardarsa da Ubangijinsa.

2. Bin mataki-mataki wajen kawar da ɓarna da farawa da wanda ya fi sauƙi sannan mai bi masa a sauƙi. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fara da da’awa da wa’azi da bayyana hujja kafin ya kai ga amfani da hannunsa.

3. Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya cimma manufarsa game da farfasa musu gumakansu, domin su da kansu sun furta cewa sun cuci kawunansu kuma suna bauta wa abin da ba shi da ikon kare kowa, kuma ba ya iya magana.

4. Shiriya baiwa ce daga Allah, ba kawai zurfin hankali ko tunani ko shekaru ke sawa a same ta ba.

5. Halaccin amfani da dabara wajen bayyana gaskiya da rushe ɓarna.

6. Marasa gaskiya sukan riƙe abin da suke tsammanin hujja ce mai goya musu baya, alhalin wannan hujja ce mai ruguza su. Dubi yadda mutanen Annabi Ibrahimu suka koma suna ce masa ai da ma ya san gumakansu ba sa magana, watau shi ya sa ya ce a tambaye su. Wannan wata hujja ce da ke tabbatar da rashin dacewar a bauta musu, ba wai tana nuna rashin gaskiyar Annabi Ibrahimu ba, kamar yadda suke zato.

7. Amfani da kakkausar magana idan har akwai buƙatar hakan kuma ba za ta haifar da wani abu mai cutarwa ba.

Suratul Anbiya (57-67)

وَتَٱللَّهِ لَأَكِيدَنَّ أَصۡنَٰمَكُم بَعۡدَ أَن تُوَلُّواْ مُدۡبِرِينَ ٥٧ فَجَعَلَهُمۡ جُذَٰذًا إِلَّا كَبِيرٗا لَّهُمۡ لَعَلَّهُمۡ إِلَيۡهِ يَرۡجِعُونَ ٥٨ قَالُواْ مَن فَعَلَ هَٰذَا بِـَٔالِهَتِنَآ إِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥٩ قَالُواْ سَمِعۡنَا فَتٗى يَذۡكُرُهُمۡ يُقَالُ لَهُۥٓ إِبۡرَٰهِيمُ ٦٠ قَالُواْ فَأۡتُواْ بِهِۦ عَلَىٰٓ أَعۡيُنِ ٱلنَّاسِ لَعَلَّهُمۡ يَشۡهَدُونَ ٦١ قَالُوٓاْ ءَأَنتَ فَعَلۡتَ هَٰذَا بِـَٔالِهَتِنَا يَٰٓإِبۡرَٰهِيمُ ٦٢ قَالَ بَلۡ فَعَلَهُۥ كَبِيرُهُمۡ هَٰذَا فَسۡـَٔلُوهُمۡ إِن كَانُواْ يَنطِقُونَ ٦٣ فَرَجَعُوٓاْ إِلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ فَقَالُوٓاْ إِنَّكُمۡ أَنتُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٦٤ ثُمَّ نُكِسُواْ عَلَىٰ رُءُوسِهِمۡ لَقَدۡ عَلِمۡتَ مَا هَٰٓؤُلَآءِ يَنطِقُونَ ٦٥ قَالَ أَفَتَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكُمۡ شَيۡـٔٗا وَلَا يَضُرُّكُمۡ ٦٦ أُفّٖ لَّكُمۡ وَلِمَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٦٧

57. “Na rantse da Allah tabbas zan shirya wa gumakanku kaidi bayan kun tafi kun ba da baya!

58. Sai ya mayar da su guntu-guntu in ban da babbansu (da ya bari) don ko sa dawo masa (su tambaye shi).

59. Suke ce: “Wane ne ya yi wa ababen bautarmu wannan (aika-aika)? Lallai shi yana daga azzalumai!”

60. (Wasu daga cikinsu) suka ce: “Mun ji wani saurayi yana ambaton su, ana ce da shi Ibrahimu.”

61. Suka ce: “(Ku je) ku zo da shi kan idon mutane don su shaidi (abin da ya aikata).”

62. (Da aka kawo shi sai) suka ce: “Yanzu kai ka aikata wannan (irin aiki) ga ababen bautarmu, ya Ibrahimu?”

63. (Ibrahimu) ya ce: “A’a, wannan babban nasu (shi) ya aikata shi, sai ku tambaye su idan ya zamana suna magana.”

64. Sai suka koma ga (zargin) kawunansu sannan suka ce: “Lallai ku dai ne azzalumai.”

65. Sannan aka juyo da kawunansu (zuwa kafirci) suka ce (da Ibrahimu): “Mun rantse haƙiƙa ka san cewa su waɗannan ba sa magana.”

66. Ya ce: “To yanzu kwa riƙa bauta wa wani ba Allah ba, wanda ba zai amfana muku komai ba kuma ba zai cuce ku ba?

67. “Tir da ku, da kuma abin da kuke bauta wa wanda ba Allah ba. To yanzu ba kwa hankalta ba?”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana labarin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa, da cewa, bayan ya gama kafa musu hujja ta hanyar wa’azi da jan hankali sai kuma ya ga ya dace ya yi amfani da wata hujjar ta zahiri da kowa zai iya ganin ta ya gane. A wannan karon rantsuwa ya yi a ransa cewa sai ya shirya wa gumakansu wata kutungwila bayan sun watse kowa ya kama gabansa sun shagala da bukukuwansu. Sai ya saɗaɗa ya shiga wurin bautarsu ya farfasa gumakansu ya yi guntu-guntu da su, in ban da babbansu, shi ya ƙyale shi don ya kafa hujja da shi, watakila idan sun dawo su tambaye shi wanda ya farfasa musu gumaka.
Bayan dawowarsu kuwa suka ga irin ɓarnar da aka yi wa gumakansu, sai suka fara tattaunawa da junansu cewa lallai duk wanda ya rugurguza musu gumakansu haka, ba shakka ya cika azzalumi. Sai nan take wasu suka ce sun taɓa jin wani saurayi mai suna Ibrahimu yana faɗar mummunar magana a kansu yana aibata su, don haka akwai yiwuwar shi ne ya ragargaza su. Sai shugabanninsu suka ba da umarni maza a je a zo da Ibrahimu gaban mutane don kowa ya ji daga bakinsa idan shi ne ya yi musu wannan aika-aika, don a samu kama shi da hujja. Da suka zo da shi suka tambaye shi ko shi ne ya yi wa gumakansu wannan aika-aikar, sai shi kuma ya so ya kama su da hujja don ya nuna musu cewa gumakansu na banza ba su da wani tasiri, sai ya nuna musu ba shi ne ya yi wannan aikin ba; wannan babban gunkin ne da ke tsaye shi ne ya yi fushi ya mammake sauran ƙananan suka dagargaje. To amma ya kamata su tambayi gumakan da kansu idan suna magana ai za su faɗa musu gaskiyar abin da ya faru.
Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sani su ma dukkansu sun san gumakan nan ba sa magana, domin ba su taɓa jin su sun yi ba, don haka sai suka koma suna tunani, suka tabbatar da cewa lallai gumakansu ba sa amfanarwa ba sa kuma iya cutarwa, don haka cutar kansu kawai suke yi da har suke bautar su ba Allah ba.
To amma sai suka dawo da baya zuwa ga kafircinsu da jayayyarsu, sai suka bayyana wa Annabi Ibrahimu cewa, ai da man ya tabbata cewa waɗannan gumakan ba sa magana, to don me zai umarce su da su tambaye su labarin abin da ya faru? Watau dai suka fassara lamarin da cewa tsokanar su yake yi yana yi musu izgili kawai.
Ana zuwa wannan gaɓar sai Annabi Ibrahimu ya shiga yi musu wa’azi yana nuna takaicinsa game da bautar wanin Allah da suke yi, su ma sun tabbatar da cewa gumakan ba za su amfana musu komai ba, ba kuma za su cutar da su da komai ba; sun kasa amfani da hankalin da Allah ya ba su don su gane irin ruɗanin da suke ciki su dawo kan hanya madaidaiciya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A ko da yaushe masu faɗa da gaskiya sukan yi zaton kawar da mai kira zuwa ga gaskiya ita ce hanyar kawo ƙarshen wannan kiran nasa. Sukan manta da cewa Allah ne yake tsaya wa wannan gaskiya ya kare ta ba wani mutum ba; yaƙi da Allah kuwa babu nasara a cikinsa samsam.

2. Duk wani sababi yana yin tasiri ne da izinin Allah. Yayin da Allah ya janye wannan tasirin daga gare shi to ba zai yi wani aiki ba. Don haka ake riƙo da sababi amma a dogara ga Allah mai gudanar da wannan sababin.

3. Kasar Sham ƙasa ce da Allah ya yawaita albarkatunsa a cikinta, domin daga cikinta ya fitar da annabawa da dama, ga ɗaki na uku a daraja, watau Masallacin Baitil Maƙdisi, sannan ya albarkace su da kayan marmari iri-iri.

4. Falalar da’awa zuwa ga Allah da ayyukan alheri.

5. An kebance salla da zakka da ambato saboda su ibadu ne masu girma da falala. Duk wanda ya kiyaye su kamar yadda aka umarce shi to zai kiyaye sauran lamuran addininsa, wanda kuwa ya tozarta su to sauran ibadunsa ma zai tozarta su. Salla ita ce mafi girman hakkin Allah a cikin ayyukan ibadu, zakka kuwa ita ce mafi girman ayyukan kyautata wa bayin Allah.

Suratul Anbiya (68-73)

قَالُواْ حَرِّقُوهُ وَٱنصُرُوٓاْ ءَالِهَتَكُمۡ إِن كُنتُمۡ فَٰعِلِينَ ٦٨ قُلۡنَا يَٰنَارُ كُونِي بَرۡدٗا وَسَلَٰمًا عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ ٦٩ وَأَرَادُواْ بِهِۦ كَيۡدٗا فَجَعَلۡنَٰهُمُ ٱلۡأَخۡسَرِينَ ٧٠
وَنَجَّيۡنَٰهُ وَلُوطًا إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ٱلَّتِي بَٰرَكۡنَا فِيهَا لِلۡعَٰلَمِينَ ٧١ وَوَهَبۡنَا لَهُۥٓ إِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ نَافِلَةٗۖ وَكُلّٗا جَعَلۡنَا صَٰلِحِينَ ٧٢ وَجَعَلۡنَٰهُمۡ أَئِمَّةٗ يَهۡدُونَ
بِأَمۡرِنَا وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡهِمۡ فِعۡلَ ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَإِقَامَ ٱلصَّلَوٰةِ وَإِيتَآءَ ٱلزَّكَوٰةِۖ وَكَانُواْ لَنَا عَٰبِدِينَ ٧٣

68. Sai suka ce: “Ku ƙone shi ku kuma taimaki allolinku in kun kasance masu aikata hakan.”

69. (Da suka jefa shi cikin wutar sai) Muka ce: “Ke wuta, ki zama sassanya da kuma aminci ga Ibrahimu!”

70. Suka yi nufin shirya masa makirci sai Muka mayar da su taɓaɓɓu.

71. Muka kuma tserar da shi, shi da Luɗu zuwa ga ƙasar da Muka yi albarka a cikinta ga talikai (watau Sham).

72. Muka kuma ba shi Is’haƙa da kuma Ya'aƙubu ƙari (wato jika). Dukkanninsu kuma Mun sanya su salihai.

73. Muka kuma sanya su shugabanni masu shiryarwa da umarninmu, Muka kuma yi musu wahayi na aikata alheri da tsai da salla da ba da zakka, sun kuwa zamanto masu bauta mana ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba mu labarin Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa bayan ya ragargaza gumakansu ya tsayar musu da hujja a aikace game da kasawar gumakan da suke bauta wa ba Allah ba, sun kuma kasa fuskantar sa da wata gamsasshiyar hujja. Don haka sai suka ga bari su yi amfani da ƙarfi wajen murƙushe shi, sai kawai shugabanninsu suka ba da umarni a jefa shi a cikin wuta a ƙona shi ƙurmus har lahira, don su nuna taimakonsu ga gumakansu da kuma ramuwa a kan abin da ya yi musu. Wannan shi ya fi dacewa idan dai har suna son yi masa wani horo da uƙuba.
Sai suka hura wuta ganga-ganga suka jefa Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a cikinta, to amma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira wutar ya ba ta umarni cewa ta juye ta koma sanyi da aminci ga Annabi Ibrahimu. Haka kuwa ya faru, wuta ta ci ta cinye ba tare da ta cutar da shi da komai ba.
Allah ya bayyana cewa mutanen Annabi Ibrahimu sun yi niyyar cutar da shi su ƙona shi har lahira, to amma Allah da ikonsa ya mayar da su su ne taɓaɓɓu a duniya da lahira, ya mayar da Ibrahimu shi da mabiyansa su ne maraubauta a duniya da lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa Ibrahimu da ɗan ɗan’uwansa Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya yi imani da shi, ya kuɓutar da su ya fitar da su daga tsakiyar waɗannan azzalumai zuwa ƙasar Sham wadda ya albarkace ta da ɗimbin albarkatu ga mutane ya kuma aiko da annabawa da yawa a cikinta.

Haka kuma ya yi wa Annabi Ibrahimu wata baiwar daban, watau ta samun haihuwar ɗansa Is'haƙa ya ƙara masa da jikansa Ya'aƙubu, kuma dukkansu shi da ɗansa da jikansa Allah ya sanya su masu ɗa'a ne da biyayya ga Allah.
Allah kuma ya bayyana wata nagarta tasu, watau yadda ya mayar da su shugabanni masu shiryar da mutane zuwa ga ayyukan alheri da ɗora su a kan hanyar bautar Allah shi kaɗai. Ya kuma yi musu wahayin cewa su dimanci ayyukan alheri su tsayar da salla yadda ya kamata su ba da zakka. Allah ya shaide su da cewa sun kasance masu bautar Allah ne da miƙa wuya a gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Aikata ayyukan alfasha yana jawo wa al'umma fushin Allah da uƙubarsa.

2. Nagarta da biyayya ga Allah su ne sababban samun rahamar Allah.

Suratul Anbiya (74-75)
وَلُوطًا ءَاتَيۡنَٰهُ حُكۡمٗا وَعِلۡمٗا وَنَجَّيۡنَٰهُ مِنَ ٱلۡقَرۡيَةِ ٱلَّتِي كَانَت تَّعۡمَلُ ٱلۡخَبَٰٓئِثَۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمَ سَوۡءٖ فَٰسِقِينَ ٧٤ وَأَدۡخَلۡنَٰهُ فِي رَحۡمَتِنَآۖ إِنَّهُۥ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٧٥

74. Luɗu kuma Muka ba shi hukunci da ilimi, Muka kuma tserar da shi daga alƙaryar nan da (mutanenta) suka zamanto suna aikata munanan ayyuka. Lallai su sun kasance mutanen banza ne fasiƙai.

75. Muka kuma shigar da shi cikin rahamarmu; lallai shi yana daga (cikin) mutane na gari.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da yawan ilimi na Shari'a da ya ba shi, da hikimar zartar da hukunce-hukunce na Shari'a a tsakanin mutane yadda ya kamata. Allah ya aika shi zuwa ga mutanensa domin ya kirawo su zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, ya hana su aikata munanan ayyuka na alfasha, musamman mummunan aikin da suka shahara da shi na neman maza. Ya zauna cikinsu tsawon lokaci yana yi musu wa'azi amma suka ƙi amsa kiransa, har sai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kifar da garinsu ya hallaka su baki ɗaya, domin sun tabbata mutanen banza ne fasiƙai. Shi kuma Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ya kuɓutar da shi da iyalansa in ban da matarsa. Ya umarce shi da ya bar garin cikin dare, suka fita daga wannan alƙarya suka tsira da taimakon Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya shigar da Annabi Luɗu cikin rahamarsa, ya tserar da shi daga azabar da ta auka wa mutanensa, kuma yana daga cikin mutane na gari masu bin umarnin Allah da hanuwa da haninsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Addu'a ce maganin kowane irin baƙin ciki da damuwa.

2. Lalacewar al'umma da rashin karɓar gyaran masu gyara shi ne sanadiyyar halakarta da gushewarta.

3. Taimakon Allah ga waliyyansa sunnarsa ce daɗaɗɗiya a tarihin kafuwar duniya.

4. Ruwan Ɗufana Allah ya siffanta shi da baƙin ciki mai girma, domin tun lokacin da ya fara ɓuɓɓugowa daga tanderu da ƙasa ya fara tsorata mutane da firgita su, duk kuma inda suka yi ƙoƙarin guje masa sai ya cim musu har ya haɗiye su suna ta nutsewa kaɗan-kaɗan har suka nutse baki ɗaya suka daina numfashi. Wannan ba shakka wani baƙin ciki ne da damuwa babba.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya nutsar da ilahirin mutanen Annabi Nuhu waɗanda ba su yi imani da shi ba, wannan ya haɗa har da makusantansa, kamar ɗansa da matarsa. Wannan wani gargaɗi ne da tsoratarwa mai girma ga Kuraishawa masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da cewa, kada kusancinsu da shi ya ruɗe su, idan azabar Allah ta zo musu ba za ta ware kowa ba.

Suratul Anbiya (76-77)

وَنُوحًا إِذْ نَادَىٰ مِن قَبْلُ فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ فَنَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥ مِنَ ٱلْكَرْبِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٧٦﴾ وَنَصَرْنَٰهُ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَآ ۚ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَوْمَ سَوْءٍ فَأَغْرَقْنَٰهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٧٧﴾

76. (Ka tuna) lokacin da Nuhu ya roƙi Ubangijinsa tun a da can, sannan Muka amsa masa (roƙonsa) Muka tserar da shi da iyalinsa daga baƙin ciki mai girma.

77. Muka kuma taimake shi bisa mutanen da suka ƙaryata ayoyinmu. Lalle su sun kasance mutanen banza, sai Muka nutsar da su gaba ɗaya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da Annabi (ﷺ) labarin Manzonsa na farko a duniya, watau Annabi Nuhu wanda Allah ya aiko shi zuwa ga mutanensa masu bautar wasu ba Allah ba. Sai da ya shekara dubu ba hamsin a cikinsu yana yi musu wa'azi ba dare ba rana, a fili da a ɓoye, to amma suka ƙi karɓar kiransa sai 'yan kaɗan daga cikinsu. Lokacin da ya tabbatar wa'azinsa ba zai amfane su ba sai ya roƙi Allah da ya hallaka su ƙwansu da ƙwarƙwatarsu, kada ya bar ko da kafiri ɗaya a bayan ƙasa. Sai ko Allah ya amsa masa addu'arsa ya tserar da shi da iyalansa muminai daga baƙin ciki mai girma, lokacin da bala'in ruwan Ɗufana ya ɓarke daga ƙasa da sama, Allah ya taimake shi a kan makircin mutanensa waɗanda suka ƙaryata ayoyin da ya ba shi masu tabbatar da gaskiyarsa. Allah ya bayyana cewa lallai su mutanen banza ne maɓarnata. Allah ya dulmiyar da su baki ɗaya a cikin ruwan Ɗufana duk suka hallaka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mai yin hukunci yakan iya yin daidai yakan kuma iya yin kuskure. Kuma babu wani zargi a tare da shi idan ya yi ijtihadi ya yi kuskure, yana da ma ladan ijtihadinsa a wurin Allah, sannan an gafarta masa kuskurensa.

2. Duwatsu da tsuntsaye dukkansu suna tasbihi tare da tsarkake mahalicci, ko da kuwa mu 'yan'adam ba ma jin tasbihinsu.

3. An ce Annabi Dawuda (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne farkon wanda ya fara ƙera silke a duniya, daga wajensa ne sauran mutane suka kwaikwaya.

4. Akwai yiwuwar cewa hanyar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya koyar da Annabi Dawuda sana'ar ƙera silke da mulmula ƙarfe hanya ce ta mu'ujiza wadda babu mai iya kwaikwayar ta kamar yadda da dama daga cikin masana tafsiri suke cewa, watau Allah ya lausasa masa ƙarfe yana kwaɓa shi kamar mai kwaɓa gari ko laka.

Yana kuma yiwuwa cewa Allah ya koyar da shi wannan sana’a ta ƙira ta hanyar da kowa ma zai iya koya, watau ta amfani da hanyoyin da aka saba wajen narkar da ƙarfe. Wannan ma’anar ta fi fitowa sarari a cikin ayoyin. Domin kuwa Allah ya bayyana al’amarin a matsayin baiwar da ya yi wa mutane har ma ya umarce su da su gode masa a kanta. Da a ce wannan sana’ar tasa mu’ujiza ce gare shi shi kaɗai babu mai iya kwaikwayon ta, to da ba ta zama baiwa ga mutane ba, da kuma babu wani amfanin faɗa musu ita, domin babu mai iya samun silke na farko da Annabi Dawuda ya ƙera. Don haka Allah yana nufin kowane silke da za a ƙera.

5. Annabi Sulaimanu ne kaɗai Allah ya hore wa sarrafa aljannu yadda ya ga dama, su yi masa hidima irin yadda yake so. Duk wanda ya yi wannan da’awar a bayansa to maƙaryaci ne.

6. Ma’anar cewar Allah ya zamanto mai kula da su aljannun shi ne, yadda Allah cikin cikakkiyar Kudurarsa ya hore su ga Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya hana su su gudu ko su yi masa taurin kai, ya sanya su su riƙa yi masa ayyuka ba tare da wani ya sani ba, ba kuma tare da suna cutar da mutane ba. Allah cikin hikimarsa ya haɗa wa Sulaimanu tsakanin hore masa su da kuma koya masa yadda zai tafiyar da al’amuransu cikin sauƙi, suka zama masu yi masa biyayya. Allah kuma ya shiga tsakaninsu da mutane ba sa cutar da su da komai. Bayan mutuwar Annabi Sulaimanu babu kuma wani wanda aka hore masa sarrafa aljannu domin amsar addu’arsa da Allah ya yi na cewa ya ba shi mulki wanda bai cancanta ya ba wa wani irinsa ba bayansa.

Suratul Anbiya (78-82)

وَدَاوُۥدَ وَسُلَيۡمَٰنَ إِذۡ يَحۡكُمَانِ فِي ٱلۡحَرۡثِ إِذۡ نَفَشَتۡ فِيهِ غَنَمُ ٱلۡقَوۡمِ وَكُنَّا لِحُكۡمِهِمۡ شَٰهِدِينَ ٧٨ فَفَهَّمۡنَٰهَا سُلَيۡمَٰنَۚ وَكُلًّا ءَاتَيۡنَا حُكۡمٗا وَعِلۡمٗاۚ وَسَخَّرۡنَا مَعَ دَاوُۥدَ ٱلۡجِبَالَ يُسَبِّحۡنَ وَٱلطَّيۡرَۚ وَكُنَّا فَٰعِلِينَ ٧٩ وَعَلَّمۡنَٰهُ صَنۡعَةَ لَبُوسٖ لَّكُمۡ لِتُحۡصِنَكُم مِّنۢ بَأۡسِكُمۡۖ فَهَلۡ أَنتُمۡ شَٰكِرُونَ ٨٠ وَلِسُلَيۡمَٰنَ ٱلرِّيحَ عَاصِفَةٗ تَجۡرِي بِأَمۡرِهِۦٓ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ٱلَّتِي بَٰرَكۡنَا فِيهَاۚ وَكُنَّا بِكُلِّ شَيۡءٍ عَٰلِمِينَ ٨١ وَمِنَ ٱلشَّيَٰطِينِ مَن يَغُوصُونَ لَهُۥ وَيَعۡمَلُونَ عَمَلٗا دُونَ ذَٰلِكَۖ وَكُنَّا لَهُمۡ حَٰفِظِينَ ٨٢

78. (Ka tuna) kuma Dawuda da Sulaimanu lokacin da suke yin hukunci a kan amfanin gona lokacin da dabbobin wasu mutane suka cinye shi da daddare, Mun kuwa zamanto Muna sane da irin hukuncin nasu.

79. Sai Muka ganar da Sulaimanu shi (hukuncin). Kuma dukkaninsu Mun ba su annabta da ilimi. Muka kuma hore wa Dawuda duwatsu da tsuntsaye, suna tasbihi tare da shi. Mun kuwa kasance Masu aikata (haka).

80. Muka kuma koya masa yadda ake ƙera silke dominku don ya kare ku lokacin yaƙinku; to shin ku masu godiya ne?

81. Sulaimanu kuwa (Muka hore masa) iska mai ƙarfi tana gudu da umarninsa zuwa ƙasar da Muka yi albarka a cikinta, (watau Sham). Mun kuwa kasance Masana ga kowanne abu.

82. Akwai kuma wasu aljannu da suke nutso don fito masa (da lu’u-lu’u) suna kuma yin wani aikin ban da wannan (kamar gine-gine); Mun zamanto kuma Masu kula da su)).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da Annabi (ﷺ) labarin annabawan Allah guda biyu, watau Dawudu da ɗansa Sulaiman waɗanda sun kasance cikin annabawan Banu Isra’ila. Allah ya ba su ilimi da hikima mai yawa, musamman wadda ta danganci hanyar warware rikice-rikicen Shari’a.

Allah ya bai wa Annabi (ﷺ) labarinsu lokacin da suka yanke wani hukunci game da wasu dabbobi da suka shiga gonar wasu manoma suka yi musu mummunar ɓarna. Allah kuma yana sane da irin hukuncin da suka yanke.
Yadda kuwa abin ya faru shi ne: Wani manomi ne ya kai ƙara wajen Annabi Dawudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) game da dabbobin wasu mutane da suka shiga gonarsa da daddare ba tare da makiyayansu ba suka cinye masa amfanin gonarsa bayan ya sha wahala a kai. Bayan masu dabbobin sun yarda da laifinsu sai Annabi Dawudu ya yanke hukunci da cewa, manomin nan zai karɓi waɗannan dabbobin a madadin kayan amfanin gonarsa da suka cinye masa bayan ya ƙiyasta ƙimar amfanin gonar daidai take da ta dabbobin. Wannan shi ne horon da ya ga ya dace ya yi wa masu dabbobi bisa ga sakacin da suka yi na rashin kula da dabbobinsu.
To amma sai Allah ya ba wa Annabi Sulaiman wata zuzzurfar fahimta dangane da wannan hukunci, sai ya bayyana cewa abin da ya dace a yi a nan shi ne a ɗauki waɗannan dabbobi a damƙa su a hannun manomi ya je da su ya ci gaba da amfani da nononsu da gashinsu, a yayin da su kuma masu dabbobi za su sake noma wa wannan manomi gonarsa har sai ta dawo kamar yadda take da farko kafin dabbobinsu su lalata ta, sannan sai su mayar masa da gonarsa da amfanin cikinta shi kuma ya dawo musu da dabbobinsu. Kowa daga ƙarshe dukiyarsa ta komo hannunsa.
Wannan ko shakka babu yana daga cikin cikar hankali da fahimta da Allah ya yi wa Sulaimanu baiwa da su. To amma don Allah ya tabbatar da cewa hukuncin da shi ma Dawudu ya yanke bai saɓa wa Ubangijinsa ba, kuma ya zama abin yabo da hikima da ilimi, sai Allah ya ƙara tabbatar da cewa dukkansu ya ba su annabta da sanin hukunce-hukuncen Shari'a, ba Sulaiman kaɗai ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wata babbar baiwa da ya yi wa Dawudu, watau yadda ya hore masa duwatsu da tsuntsaye waɗanda suke yin tasbihi tare da shi duk lokacin da suka ji muryarsa yana yi. Allah ya tabbatar da cewa wannan aikinsa ne ba na wani ba.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari ya ce Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Ya Aba Musa, haƙiƙa an ba ka sauti mai daɗi irin sautin Dawud." [Bukhari #5048 da Muslim #793].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata baiwar daban da ya ƙara wa Annabi Dawuda (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), watau yadda ya ba shi ikon sarrafa ƙarfe, yana mulmula shi yadda ya ga dama, ya koyar da shi sana'ar ƙera silke na mayaƙa don kariya daga sara ko suka a fagen daga. Daga wannan lokacin 'yan'adam suka fahimci wannan sana'a suka riƙe ta a ko'ina. Allah ya bayyana cewa wannan ni'ima ce ga mutane da ya wajaba su gode wa Allah a kanta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi ma Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) akwai wata ƙarin baiwa da ya yi masa baya ga baiwar fahimta. Allah ya hore masa ikon sarrafa iska wadda take tafiya da shi, idan ya ga dama ta yi gudu da ƙarfi idan kuma ya so ya umarce ta ta tafi a sannu gwargwadon buƙatarsa. Takan ɗauke shi da shi da rundunarsa zuwa duk inda ya buƙaci zuwa a faffaɗar masarautarsa mai albarka, watau ƙasar Sham inda babbar cibiyar sarautarsa take. Allah ya tabbatar da cewa ya san komai game da waɗannan annabawa da duk abin da ya ba su na ilimi da hikima da sarauta.
Sannan Allah ya bayyana cewa ya kuma hore wa Sulaimanu ikon sarrafa aljannu da sanya su su yi masa hidima irin wadda ya buƙata daga gare su. Daga cikinsu akwai waɗanda aikinsu kawai shi ne nutso a ƙarƙashin ruwa suna fito masa da albarkatu iri daban-daban kamar lu'ulu'u da marjani. Wasu kuma ba su da wani aiki sai yi masa manyan gine-gine da mutum-mutumi da ganuwoyi da makamantansu. Allah ya bayyana cewa shi ne mai tsare da su, yana kuma sane da adadinsu da ayyukansu, babu kuma mai iya guduwa daga cikinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah yakan jarrabi wasu annabawansa da rashin lafiya ko talauci ko rasuwar ‘ya’ya da makamantansu.

2. Komawa ga Allah da yawan addu’a shi ne maganin duk wata musiba.

3. Daga cikin hanyoyin tawassuli ga Allah babu kamar addu’a, inda bawa yake bayyana halin matsin da yake ciki.

Suratul Anbiya (83-84)

*وَأَيُّوبَ إِذْ نَادَىٰ رَبَّهُۥٓ أَنِّي مَسَّنِيَ ٱلضُّرُّ وَأَنتَ أَرْحَمُ ٱلرَّٰحِمِينَ ﴿٨٣﴾ فَٱسْتَجَبْنَا لَهُۥ فَكَشَفْنَا مَا بِهِۦ مِن ضُرٍّ ۖ وَءَاتَيْنَٰهُ أَهْلَهُۥ وَمِثْلَهُم مَّعَهُمْ رَحْمَةً مِّنْ عِندِنَا وَذِكْرَىٰ لِلْعَٰبِدِينَ ﴿٨٤﴾

83. Kuma (ka tuna) Ayyuba lokacin da ya roƙi Ubangijinsa (yana cewa): “Lallai cuta ta same ni, Kai ne kuwa Mafi jin ƙan masu jin ƙai!”

84. Sai Muka amsa masa (roƙonsa) sannan Muka yaye cutar da take tare da shi, Muka kuma ba shi (madadin) iyalinsa (da ya rasa) da kuma kwatankwacinsu tare da su don jin ƙai daga gare Mu da kuma wa’azi ga masu bauta (ga Allah).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tunatar da Annabi (ﷺ) labarin Annabi Ayyuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jarrabe shi da bala’o’i iri-iri na tsananin rashin lafiya da mutuwar iyalansa da lalacewar dukiyarsa. Ya zauna tsawon lokaci cikin wannan jarrabar yana mai haƙuri da dangana da fawwala wa Allah komai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya ɗaga murya ya roƙe shi da cewa cuta ta same shi, don haka ya yaye masa ita, ya tausaya masa domin tausayinsa ya fi na duk wani mai tausayi.
Sai ko Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa wa Ayyuba addu’arsa, ya kuma yaye masa cutar da ke tare da shi, sannan ya dawo masa da iyalansa da ya rasa, ya kuma ƙara masa wasu kamarsu. Allah ya tabbatar da cewa ya yi haka ne domin rahama daga wajensa da kuma tunatarwa da wa’azi ga bayinsa masu miƙa wuya gare shi don su ma su koyi haƙuri irin na Annabi Ayyuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Annabin Allah Ayyuba ya zauna cikin bala’i tsawon shekara goma sha takwas. Na kusa da na nesa duk suka guje masa sai wasu ‘yan’uwansa mutum biyu waɗanda suka fi kowa shaƙuwa da shi su ne suke zuwa wajensa safe da yamma. Sai wata rana ɗayansu ya faɗa wa ɗan’uwansa cewa: “Lallai Ayyuba ya yi wani zunubi ne da ba wanda ya taɓa yin irinsa.” Sai ɗan’uwan nasa ya tambaye shi me ya sa ya faɗi wannan maganar tasa? Sai ya amsa masa da cewa: “Idan ka lura za ka ga yau kimanin shekara goma sha takwas ke nan yana cikin wannan bala’in, Allah bai tausaya masa ya yaye masa shi ba.” Da yamma ta yi suka je wajen Ayyuba, wannan mutum bai iya haɗiye wannan maganar ta ɗan’uwansa ba a kan Annabi Ayyuba har sai da ya faɗa masa ita. Ayyuba ya ce: “To ni dai ban san wannan magana da kake faɗa ba. Abin da dai na riga na sani shi ne, ni mutum ne da a duk lokacin da na wuce ta gaban mutum biyu suna jayayya a junansu ɗayansu ya yi rantsuwa da Allah, to idan na dawo gida sai na yi masa kaffara don gudun kada ko ya yi rantsuwan nan ba bisa gaskiya ba.”
Ayyuba ya zamanto yana fita bayan gari don biyan buƙatarsa, idan ya gama sai matarsa ta kamo hannunsa (domin su dawo gida). Wata rana sun fita sai matarsa ta ga ya daɗe bai dawo ba, to a lokacin Allah ne ya yi masa wahayi cewa: “Ka hauri ƙasa da ƙafarka, wannan ruwan wanka ne mai sanyi da na sha.” Da matarsa

ta jira shi ba ta gan shi ba sai ta bi bayansa, sai ga shi yana tahowa, Allah ya yaye masa cutarsa, ya zamanto ya ma fi da kyau. Da ganin sa sai ta ce: “Bawan Allah, Allah ya yi maka albarka, ko ka ga Annabin Allah ɗin nan marar lafiya? Kai duk da haka ni ban taɓa ganin wani mutum da ya yi kama da shi ba lokacin da yake da lafiya irinka.” Sai ya ce: “Ni ne shi kuwa.” [Ibn Hibban #2898 da Abu Ya’ala #3617].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa waɗannan annabawan su uku wuri guda a nan domin sun yi tarayya a kan siffa ta haƙuri.

2. Nagartar bawa ita ce sababin samun rahamarsa.

3. Falalar haƙuri da juriya.

Suratul Anbiya (85-86)

وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِدۡرِيسَ وَذَا ٱلۡكِفۡلِۖ كُلّٞ مِّنَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٨٥ وَأَدۡخَلۡنَٰهُمۡ فِي رَحۡمَتِنَآۖ إِنَّهُم مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٨٦

85. (Ka tuna) kuma Isma’ila da Idrisa da kuma Zulkifli; dukkansu suna cikin masu haƙuri.

86. Muka kuma shigar da su cikin rahamarmu; lalle su suna daga bayi na gari.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba wa Annabi (ﷺ) labarin wasu annabawa su uku daga cikin zaɓaɓɓun bayinsa, watau Isma’ila da Idrisa da Zulkifli. Allah ya yabe su da nagarta da haƙuri a kan bin sa da guje wa saɓa masa, ya kuma shigar da su cikin rahamarsa, watau ya ba su annabta sannan ya shigar da su Aljannarsa, domin kasancewarsu bayin Allah na gari waɗanda suka gyara zahirinsu da baɗininsu da kyawawan ayyuka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bawa ya amsa laifinsa, ya yi kuma bayanin halinsa yana daga cikin sababban karɓar addu’arsa.

2. Biyayya ga Allah a cikin halin yalwa da ni’ima yana daga cikin sababban samun taimakon Ubangiji yayin da bawa ya shiga cikin halin tsanani.

3. Falalar tasbihi da Tauhidi.

4. Bawa ba ya iya kuɓuta gaba ɗaya daga zaluntar kansa a wani lokaci.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin amsa wa muminai addu’arsu yayin da suka shiga cikin wani ƙunci da tsanani kamar yadda ya amsa wa bawansa Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Suratul Anbiya (87-88)

وَذَا ٱلنُّونِ إِذ ذَّهَبَ مُغَٰضِبٗا فَظَنَّ أَن لَّن نَّقۡدِرَ عَلَيۡهِ فَنَادَىٰ فِي ٱلظُّلُمَٰتِ أَن لَّآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنتَ سُبۡحَٰنَكَ إِنِّي كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٨٧ فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ وَنَجَّيۡنَٰهُ مِنَ ٱلۡغَمِّۚ وَكَذَٰلِكَ نُنجِي ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٨٨ وَذَا ٱلنُّونِ إِذ ذَّهَبَ مُغَٰضِبٗا فَظَنَّ أَن لَّن نَّقۡدِرَ عَلَيۡهِ فَنَادَىٰ فِي ٱلظُّلُمَٰتِ أَن لَّآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنتَ سُبۡحَٰنَكَ إِنِّي كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٨٧ فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ وَنَجَّيۡنَٰهُ مِنَ ٱلۡغَمِّۚ وَكَذَٰلِكَ نُنجِي ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٨٨

87. Kuma (ka tuna) ma'abocin kifi (wato Yunusa) lokacin da ya tafi yana cike da fushi, sannan ya zaci cewa ba za Mu ƙuntata masa ba, sai ya kira (Mu) a cikin duffai yana cewa: "Ba wani abin bauta da gaskiya sai Kai (ya Allah), tsarki ya tabbata a gare Ka, lallai ni na kasance cikin azzalumai!"

88. Sai Muka amsa masa Muka kuma tserar da shi daga baƙin ciki. Kamar haka kuwa Muke tserar da muminai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba wa Annabi (ﷺ) labarin Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da ya ƙaurace wa mutanensa da Allah ya aiko shi wajensu yana cike da fushi, ba tare da samun izini daga Ubangijinsa na ƙaura ce musu ba. Ya ƙaura ce ne saboda sun doge a kan kafirci da saɓon Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai yi zaton cewa Allah zai ƙuntata masa don ya bar jama'arsa kafirai ba. To amma sai Allah ya jarrabe shi da faɗawa cikin ƙunci da tsanani yayin da kifi ya haɗiye shi. To a nan ne fa ya shiga addu'a yana cikin duhu a kan duhu; ga duhun dare ga na kogi ga kuma na cikin kifi, inda yake cewa: "Ya Allah babu abin bauta wa da gaskiya sai kai; tsarki ya tabbata gare ka, lallai ni na kasance daga cikin azzalumai."
Sai ko Allah ya bayyana cewa ya amsa masa addu'arsa, ya tserar da shi daga tsananin da yake ciki, ya fito da shi daga cikin cikin kifi. Allah kuma ya tabbatar da cewa kamar yadda ya tserar da Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kamar haka ne yake tserar da muminai yayin da suka faɗa cikin wani tsanani ko musiba.

An karɓo daga Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Addu'ar ma'abocin kifi (Yunus (Amincin Allah ya tabbata a gare shi)) lokacin da ya roƙi Allah yana cikin cikin kifi cewa:
﴿ لَا إِلَهَ إِلَّا أَنْتَ سُبْحَانَكَ إِنِّي كُنْتُ مِنَ الظَّالِمِينَ ﴾
Babu wani Musulmi da zai roƙi Allah da ita game da wata buƙatarsa sai Allah ya amsa masa." [Ahmad #1462 da Tirmizi #3505].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar neman samun haihuwar ɗa wanda zai rayu bayan mutuwar mahaifansa, don ya gaje su wajen aikin alheri da yi musu addu'a.

2. Samun haihuwa wata kyauta ce daga Allah, don haka ya wajaba bawa ya yi wa Allah godiya a kanta.

3. Wajibi ne a kan bawa mumini ya bauta wa Allah tare da kyakkyawan fata da tsoro.

4. Falalar gaggawa zuwa ga aikata ayyukan alheri.

5. Yana daga cikin amfanin zama da mutanen kirki samun wata albarka daga Allah a sanadiyyarsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gyara mahaifar matar Annabi Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a sanadiyyar amsa masa addu'arsa ta samun ɗa namiji.

Suratul Anbiya (89-90)
وَزَكَرِيَّآ إِذۡ نَادَىٰ رَبَّهُۥ رَبِّ لَا تَذَرۡنِي فَرۡدٗا وَأَنتَ خَيۡرُ ٱلۡوَٰرِثِينَ٨٩ فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ وَوَهَبۡنَا لَهُۥ يَحۡيَىٰ وَأَصۡلَحۡنَا لَهُۥ زَوۡجَهُۥٓۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَيَدۡعُونَنَا رَغَبٗا وَرَهَبٗاۖ وَكَانُواْ لَنَا خَٰشِعِينَ٩٠

89. (Ka tuna) kuma Zakariya'u lokacin da ya roƙi Ubangijinsa (cewa): "Ya Ubangijina, kada Ka bar ni ni kaɗai (ba magaji), Kai ne kuwa Fiyayyen magada."

90. Sai Muka amsa masa Muka ba shi Yahya, Muka kuma gyara masa (mahaifar) matarsa. Lallai su sun kasance suna gaggawa wajen yin alherai, suna kuma roƙon Mu suna masu kwaɗayin (rahamarmu) masu kuma tsoron (azabarmu), sun kuma zamanto masu ƙaskantar da kai gare Mu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba wa Annabi (ﷺ) labarin Annabi Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda shi ma ya faɗa cikin wata damuwa ta rashin samun ɗa magaji wanda zai maye gurbinsa wajen ilmantar da Banu Isra'ila da yi musu wa'azi kamar yadda yake yi, har girma ya riske shi. Bugu da ƙari kuma ga matarsa bakarara ce ba ta haihuwa, ita ma kuma ta manyanta. To amma ganin Maryam Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karrama ta da wasu karamomi na ban mamaki, (Dubi *Suratu Ali Imrana*, aya ta 37 zuwa ta 41), sai shi ma ya yi addu'a da cewa: "Ya Ubangijina, kada ka bar ni ni kaɗai ba tare da ka ba ni ɗa ba, alhalin kai ne Fiyayyen masu wanzuwa, don haka ka arzuta ni da samun ɗa wanda zai rayu bayana.
Sai Allah ya bayyana cewa ya karɓi addu'arsa ya ba shi kyautar ɗa namiji, har ma ya raɗa masa suna Yahya. Bugu da ƙari kuma ya gyara masa matarsa bakarara ta koma mai haihuwa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin yadda wannan gida na Annabi Zakariyya ya kasance, watau shi da matarsa da ɗansa Yahya. Sun zamanto suna gaggawar aikata ayyukan alheri, tare da roƙon Allah da bauta masa, domin fatan samun lada a wajensa da kuma tsoron azabarsa, suna kuma masu ƙaskantar da kai ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar Maryamu da ɗanta Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gwama labarin Maryamu da ɗanta Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kuma labarin Zakariyya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ɗansa Yahya (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) inda ya fara ambaton labarin Zakariyya don ya zama kamar shimfiɗa ce ga labarinta, domin labarinsa yana nuna samuwar ɗa daga mutumin da ya tsufa tukuf, kuma matarsa bakarara wadda tun tana yarinya ma ba ta haihu ba. Bayansa ne kuma ya kawo labarin da ya fi wannan ban mamaki, wanda ya ƙunshi samar da ɗa daga mace ita kaɗai ba tare da namiji ba. Har wa yau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gwama labarun guda biyu, a cikin *Suratu Ali Imran* da kuma *Suratu Maryam.*

3. Falalar kamun kai ga 'ya mace, kuma hakan yakan kasance sanadiyyar ɗaukakarta da zurriyyarta.

Suratul Anbiya (91)

وَٱلَّتِيٓ أَحۡصَنَتۡ فَرۡجَهَا فَنَفَخۡنَا فِيهَا مِن رُّوحِنَا وَجَعَلۡنَٰهَا وَٱبۡنَهَآ ءَايَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ ٩١

91. (Ka tuna) kuma wadda ta tsare matancinta, sai Muka yi busa a cikinta daga Ruhinmu, Muka kuma sanya ta ita da ɗanta aya ga talikai.

A wannan ayar kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba wa Annabi (ﷺ) labarin Maryamu da ɗanta Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ita ma da irin karramawar da ya yi mata yayin da ta kame kanta tana ta bautar Allah, sai ya aiko Mala'ika Jibrilu ya yi mata busa ta ɗauki cikin Annabi Isa (Amincin Allah ya

tabbata a gare shi), [Kamar yadda ya bayyana cikakken labarin a cikin *Suratu Maryam* daga aya ta 16 zuwa ta 33].
Sai kuma ya bayyana cewa Maryamu da ɗanta Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun zamanto wata alama ce ga mutane wadda take tabbatar da cikakkiyar Kudirar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da nuna cewa babu abin da zai gagare shi, don haka ya halicci Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba tare da uba ba.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan annabawa da manzanni sun haɗu a kan Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta.

2. Riƙo da Tauhidi shi ne kaɗai abin da zai haɗa kan al'umma.

3. Rarrabuwar 'yan'adam ta samo tushe ne daga rarrabuwa a kan kaɗaita Allah da bauta da akasinsa.

4. Imani da Allah sharaɗi ne na karɓar kyawawan ayyuka.

Suratul Anbiya (92-94)
إِنَّ هَٰذِهِۦٓ أُمَّتُكُمْ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَأَنَا۠ رَبُّكُمْ فَٱعْبُدُونِ ﴿٩٢﴾ وَتَقَطَّعُوٓا۟ أَمْرَهُم بَيْنَهُمْ ۖ كُلٌّ إِلَيْنَا رَٰجِعُونَ ﴿٩٣﴾ فَمَن يَعْمَلْ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَهُوَ مُؤْمِنٌ فَلَا كُفْرَانَ لِسَعْيِهِۦ ۖ وَإِنَّا لَهُۥ كَٰتِبُونَ ﴿٩٤﴾

92. Lallai wannan addini naku guda ɗaya ne (wato Musulunci), kuma Ni ne Ubangijinku, to ku bauta min.

93. Sannan sai suka rarraba al'amarinsu (na addini) a tsakaninsu; dukkaninsu dai masu komowa ne zuwa gare Mu.

94. To duk wanda ya aikata kyawawan ayyuka alhali kuwa shi mumini ne, to babu musantawa ga aikinsa, lallai kuma Mu Masu rubuta masa shi ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, labarun da aka bayar na wasu daga cikin annabawan Allah, bayani ne da ya danganci abu guda, shi ne addinin Allah na Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta, shi ne kuma Musulunci, addinin da ya zaɓar wa mutane baki ɗaya, ya kuma tabbatar musu da cewa shi ne Ubangijinsu Mahaliccinsu mai kula da duk al'amuransu. Don haka su tsantsanta bauta gare shi shi kaɗai kada su haɗa shi da komai.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, duk da irin kiran da annabawa suka yi zuwa ga hanya guda ɗaya ta Tauhidi, to amma duk da haka sai da mutane suka rarrabu, wasu suna ɗayanta Allah wasu kuma suna haɗa shi da wasu abubuwa wajen bauta, watau wasu muminai wasu kuma suka kafirce. Allah kuma ya tabbatar musu da cewa gaba ɗayansu gare shi za su koma ranar alƙiyama ya yi wa kowa sakayya a kan ayyukansa masu kyau da munana.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wanda ya yi kyawawan ayyuka daga cikinsu yana mai imani da Allah da manzanninsa da ranar lahira, to wannan ba za a yi masa runton aikinsa mai kyau ba, za a yi masa kyakkyawar sakayya ne a kai, a kuma ninninka masa ladansa, ya same shi rubuce a cikin littafin ayyukansa ranar alƙiyama, ya yi farin ciki da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Buɗe ganuwar Yajuju da Majuju da fitowarsu yana daga cikin manyan alamomin kusantowar tashin alƙiyama.

2. Yajuju da Majuju ƙabilu biyu ne masu yawan gaske.

3. Yajuju da Majuju suna da matuƙar sauri wajen karaɗe duniya, ko dai saboda haka Allah ya halicce su ko kuma saboda wata na'ura da za su yi amfani da ita wajen tafiyen-tafiyensu.

4. Babu wata tazara mai tsawo tsakanin bayyanar Yajuju da Majuju da tashin alƙiyama.

5. Nadamar azzalumai a ranar alƙiyama lokacin da nadamar ba za ta amfane su da komai ba.

Suratul Anbiya (95-97)
وَحَرَٰمٌ عَلَىٰ قَرۡيَةٍ أَهۡلَكۡنَٰهَآ أَنَّهُمۡ لَا يَرۡجِعُونَ ٩٥ حَتَّىٰٓ إِذَا فُتِحَتۡ يَأۡجُوجُ وَمَأۡجُوجُ وَهُم مِّن كُلِّ حَدَبٖ يَنسِلُونَ ٩٦ وَٱقۡتَرَبَ ٱلۡوَعۡدُ ٱلۡحَقُّ فَإِذَا هِيَ شَٰخِصَةٌ أَبۡصَٰرُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يَٰوَيۡلَنَا قَدۡ كُنَّا فِي غَفۡلَةٖ مِّنۡ هَٰذَا بَلۡ كُنَّا ظَٰلِمِينَ ٩٧

95. Kuma haramun ne ga (duk) wata al'umma da Muka hallaka cewa za su komo (duniya).

96. Har sai lokacin da aka buɗe Yajuju da Majuju, su kuwa za su gangaro ne ta kowanne tudu.

97. Kuma alƙawarin gaskiya ya gabato, sai ga shi idanuwan waɗanda suka kafirta sun yi zuru-zuru (suna cewa): "Kaiconmu! Haƙiƙa mun kasance cikin gafala game da wannan (ranar); a'a, kai mu dai mun kasance azzalumai ne!"

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk mutanen alƙaryar da suka kafirce wa Allah har ya hallaka su, to ba ta yadda za a dawo da su duniya wai don a ba su damar su tuba su gyara kurakuransu, duk kuwa magiyar da za su yi wannan abu sam ba zai taɓa faruwa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa lokaci na nan tafe yayin da za a buɗe wa Yajuju da Majuju ƙofar fitowa daga cikin ganuwar da Zulƙarnaini ya gina don katange tsakaninsu da mutane. Idan kuwa an buɗe ta to za su fito su yi ta kwararowa daga kowane tudu cikin matuƙar sauri don su yaɗa ɓarna a bayan ƙasa.
Bayanin Yajuju da Majuju ya gabata a *Suratul Kahafi* aya, ta 94 zuwa ta 98.

An karɓo daga Annawwas ɗan Sam'an (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "....Sannan Allah zai aiko da Yajuju da Majuju (su kuwa za su gangaro ne ta kowanne tudu), sai na farkonsu su wuce ta gaban ƙoramar Ɗabariyya sai su shanye ruwanta, na ƙarshensu kuma su zo wucewa sai su riƙa cewa: "Da fa wurin nan akwai ruwa." Sai a tsare Annabin Allah Isa da mabiyansa, har ya zamanto kan bijimin sa a wurin ɗayansu a ranar ya fi a ba shi dinari ɗari. Sai Allah ya aiko wa Yajuju da Majuju wasu tsutsotsi su baibaye wuyayensu sai kawai su wayi gari duk a mace kamar mutuwar rai guda. Sannan Annabin Allah Isa da sahabbansa su sauko ƙasa (daga kan duwatsun da suka fake) sai ya zamana babu daidai da wuri ɗani ɗaya a bayan ƙasa face mummunan warin Yajuju da Majuju ya cika shi. Sai Annabi Isa da sahabbansa su roƙi Allah sai Allah ya aiko da wasu tsuntsaye manya-manya kamar wuyan raƙuma su ɗauke gawawwakinsu su jefar da su inda Allah ya ga dama. Sannan sai Allah ya aiko da wani ruwan sama wanda ginin laka ko na

gashin dabbobi ba zai iya tare shi ba sai ya wanke bayan ƙasa da shi ta yi haske kamar madubi...” [Muslim #2937].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, bayyanar Yajuju da Majuju alama ce ta kusantowar lokacin alƙiyama, sai abubuwan cikinta na ban tsoro da wahalhalunta su fara bayyana. A ranar ne tsoro zai cika zukatan kafirai, idanuwansu su fito su yi zuru-zuru, daga nan sai su fara kirawo wa kawunansu hallaka, suna nuna nadamar irin rayuwar shagala da gafala da suka yi a duniya, ba su yi wa wannan rana kowane irin tanadi ba, in ban da kafirci da ayyukan saɓon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda aka bauta masa ya kuma yarda da bautar to shi ɗan wuta ne a lahira.

2. Hikimar Allah ta shigar da gumaka cikin wutar Jahannama duk da cewa su abubuwa ne daskararru marasa hankali kuma babu wani zunubi a kansu, shi ne don ƙara tabbatar da ƙaryar waɗanda suka ɗauke su a matsayin alloli, sannan kuma a yi musu azaba da su.

Suratul Anbiya (98-100)
إِنَّكُمۡ وَمَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ حَصَبُ جَهَنَّمَ أَنتُمۡ لَهَا وَٰرِدُونَ ٩٨ لَوۡ كَانَ هَٰٓؤُلَآءِ ءَالِهَةٗ مَّا وَرَدُوهَاۖ وَكُلّٞ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٩٩ لَهُمۡ فِيهَا زَفِيرٞ وَهُمۡ فِيهَا لَا يَسۡمَعُونَ ١٠٠

98. (Sai a ce da su): “Lallai ku da abin da kuke bauta wa ba Allah ba, (duka) makamashin Jahannama ne, kuma ku masu shigar ta ne.”

99. Da waɗancan (gumakan) sun kasance alloli (na gaske) da ba su shiga cikinta ba, dukkaninsu kuwa madawwama ne a cikinta.

100. Suna ta ƙaraji a cikinta, alhali kuwa su a cikinta ba sa jin (sautin komai).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai masu bautar wasu ba Allah ba cewa, da su da gumakan ko mutane da aljannun da suke bauta wa dukkansu za su zama makamashin wutar Jahannama a ranar alƙiyama, domin Allah zai tarkata su gaba ɗayansu ya watsa su a cikinta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, da a ce abubuwan da mushirikan suka bauta wa ba Allah ba gaskiya ne, to da ba su shiga wutar tare da masu bautar su ba. To amma da yake na ƙarya ne dukkansu za su shiga wuta kuma su dawwama a cikinta har abada.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa za su gamu da matsananciyar azaba a wutar Jahannama, wadda za su cika ta da ƙaraji da ihu ta yadda ba za su ji komai ba in ba wannan ife-ifen ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda aka bauta masa ba tare da yardarsa ba, to Allah ba zai kama shi da laifin wannan bautar da aka yi masa ba.

2. Kasancewar Allah mai cika alƙawarinsa ne wannan albishir ne ga Annabi da muminai cewa zai cika musu alƙawarinsa na ba su nasara da kafuwa a bayan ƙasa. Haka kuwa shi ne ya tabbata.

Suratul Anbiya (101-104)

إِنَّ ٱلَّذِينَ سَبَقَتۡ لَهُم مِّنَّا ٱلۡحُسۡنَىٰٓ أُوْلَٰٓئِكَ عَنۡهَا مُبۡعَدُونَ ١٠١ لَا يَسۡمَعُونَ حَسِيسَهَاۖ وَهُمۡ فِي مَا ٱشۡتَهَتۡ أَنفُسُهُمۡ خَٰلِدُونَ ١٠٢ لَا يَحۡزُنُهُمُ ٱلۡفَزَعُ ٱلۡأَكۡبَرُ وَتَتَلَقَّىٰهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُۖ هَٰذَا يَوۡمُكُمُ ٱلَّذِي كُنتُمۡ تُوعَدُونَ ١٠٣ يَوۡمَ نَطۡوِي ٱلسَّمَآءَ كَطَيِّ ٱلسِّجِلِّ لِلۡكُتُبِۚ كَمَا بَدَأۡنَآ أَوَّلَ خَلۡقٖ نُّعِيدُهُۥۚ وَعۡدًا عَلَيۡنَآۚ إِنَّا كُنَّا فَٰعِلِينَ ١٠٤

101. Lalle waɗanda kalmarmu mafi kyau (ta cewa su ‘yan Aljanna ne) ta riga ta tabbata gare su, waɗannan waɗanda ake nesantawa ne daga gare ta (wutar).

102. Ba za su ji hargowarta ba, kuma su masu dawwama ne cikin abin da ransu yake so.

103. Babbar firgitar (wannan ranar) ba ta samun su, kuma mala’iku za su tare su, (suna cewa): “Wannan ita ce ranar taku wadda kuka zamanto ana yi muku alƙawarinta (a duniya).”

104. (Ita ce) ranar da za Mu naɗe sama kamar naɗin marubuci ga takardu. Kamar yadda Muka ƙagi halitta da farko (haka) za Mu mai da ita. Wannan alƙawari ne da Muka ɗauka. Lallai Mun kasance Masu aikata (haka).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa bayinsa waɗanda ya yi wa kyakkyawan sakamako da gidan Aljanna saboda imaninsu da kyawawan ayyukansu, zai nesanta su daga shiga wutar Jahannama, ba ma za su jiyo ɗuriyarta ba, sannan suna cikin ni’imar gidan Aljanna suna more duk abin da suka yi sha’awa na kayan jin daɗi, kuma za su dawwama a cikinta har abada. Babu kuma wani abin tsoro da zai tashi hankalinsu, lokacin da wutar Jahannama za ta mamaye ‘ya’yanta. Mala’iku kuma za su riƙa taryar su da yi musu marhabun, suna jaddada musu cewa, wannan shi ne yinin da aka yi musu alƙawarin zuwansa tun suna duniya, sai su yi musu albishir da kyakkyawan sakamako da za su samu a wannan rana.
Wasu daga cikin masana tafsiri, kamar Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) sun bayyana cewa waɗannan ayoyi sun sauka ne don mayar da martani ga mushirikai yayin da suka ce, idan har abubuwan da suke bauta wa ba Allah ba za a shigar da su wuta kamar yadda ya gabata a ayoyin baya, to ke nan har da mala’iku da Annabi Isa da mahaifiyarsa Maryamu da wasu suke bauta musu tare da Allah, su ma duk za su shiga wuta. Sai Allah ya bayyana musu cewa waɗannan duk nagari ne waɗanda suka yi imani da Allah kuma ba su amince da bautar da aka yi musu ba, don haka su ‘yan Aljanna ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta ranar lahira da cewa ita ce ranar da zai naɗe sama kamar yadda ake naɗe takarda da abin da take ɗauke da shi na rubutu. Kuma a ranar ne zai tattara ɗaukacin halittu a cikin yanayin da ya fara halittar su. Ya tabbatar da cewa wannan alƙawari ne da ya yi kuma sai ya cika shi babu makawa, domin ba ya saba duk wani alƙawari da ya yi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nagarta ita ce hanyar samun kafuwa a bayan ƙasa.

2. Aiko Manzon Allah (ﷺ) da shari’arsa da sunnarsa rahama ne ga duniya baki ɗaya.

3. Aiko Annabi (ﷺ) rahama ce har ga kafirai, domin a dalilinsa ne Allah bai hallaka su hallakawa ta gaba ɗaya ba.

4. Kaɗaita Allah da bauta, watau hanyar Tauhidi shi ne jigon saƙon da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi.

5. Annabi (ﷺ) bai san gaibu ba.

6. Jinkirin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa kafirai ba wani abu ne ba face talala ce yake yi musu domin su ci gaba da kafircinsu da ƙaryatawarsu.

Suratul Anbiya (105-112)

وَلَقَدۡ كَتَبۡنَا فِي ٱلزَّبُورِ مِنۢ بَعۡدِ ٱلذِّكۡرِ أَنَّ ٱلۡأَرۡضَ يَرِثُهَا عِبَادِيَ ٱلصَّٰلِحُونَ ١٠٥ إِنَّ فِي هَٰذَا لَبَلَٰغٗا لِّقَوۡمٍ عَٰبِدِينَ ١٠٦ وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا رَحۡمَةٗ
لِّلۡعَٰلَمِينَ ١٠٧ قُلۡ إِنَّمَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّسۡلِمُونَ ١٠٨ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقُلۡ ءَاذَنتُكُمۡ عَلَىٰ سَوَآءٖۖ وَإِنۡ أَدۡرِيٓ أَقَرِيبٌ أَم
بَعِيدٞ مَّا تُوعَدُونَ ١٠٩ إِنَّهُۥ يَعۡلَمُ ٱلۡجَهۡرَ مِنَ ٱلۡقَوۡلِ وَيَعۡلَمُ مَا تَكۡتُمُونَ ١١٠ وَإِنۡ أَدۡرِي لَعَلَّهُۥ فِتۡنَةٞ لَّكُمۡ وَمَتَٰعٌ إِلَىٰ حِينٖ ١١١ قَٰلَ رَبِّ ٱحۡكُم
بِٱلۡحَقِّۗ وَرَبُّنَا ٱلرَّحۡمَٰنُ ٱلۡمُسۡتَعَانُ عَلَىٰ مَا تَصِفُونَ ١١٢

105. Kuma haƙiƙa Mun rubuta cikin saukakkun littattafai bayan (an rubuta a Lauhul-Mahfuzu) cewa, ita ƙasa bayina na gari ne za su gaje ta.

106. Lallai a cikin wannan (Alƙur'ani) akwai isar da saƙo ga mutane masu bauta.

107. Ba Mu aiko ka ba sai don rahama ga talikai.

108. Ka ce (da su): "Abin da kawai ake yiwo min wahayinsa (shi ne) lallai abin bautar ku Allah ne Guda Ɗaya; to shin ko za ku miƙa wuya?"

109. To idan sun ba da baya sai ka ce (da su): "Na sanar da ku cewa ni da ku muna kan abu ɗaya ne (wato ta-ware). Kuma ni ban sani ba, shin abin da ake yi muku alƙawari da shi kusa yake ko kuwa nesa?

110. "Lalle Shi (Allah) Yana sane da (abin da kuke) bayyanawa na magana Yana kuma sane da abin da kuke ɓoyewa.

111. "Kuma ban sani ba ko watakila shi (jinkirta azabtar da ku) fitina ne a gare ku da kuma jin daɗi zuwa wani ɗan lokaci.

112. (Annabi Muhammadu) ya ce: "Ya Ubangijina, Ka yi hukunci (tsakanina da kafirai) da gaskiya. Ubangijinmu kuwa (Shi ne) Ar-Rahamanu Wanda ake neman taimakonsa a kan abin da kuke siffantawa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya riga ya rubuta a cikin littattafan farko da ya saukar wa manzanninsa bayan ya rubuta a cikin Lauhul Mahfuzi cewa bayin Allah na ƙwarai masu biyayya ga Allah da Manzonsa, watau al'ummar Annabi (ﷺ) su ne za su gaje ƙasa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa, Alƙur'ani da ya saukar cike yake da wa'azi da tunatarwa kuma isar da saƙo ne ga mutane masu bauta wa Allah bisa ga abin da ya shar'anta musu. Su kaɗai ne kuma za su amfana da shi. Haka kuma bai aiko Manzon Allah (ﷺ) ba sai don ya zama rahama ga

duniya baki ɗaya, saboda kwaɗayin ganin sun shiriya, domin su kuɓuta daga azabar Allah ta duniya da ta lahira.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wasu sun nemi Manzon Allah (ﷺ) ya yi mummunar addu'a ga mushirikai, sai ya ce: "Lallai ni ba a aiko ni don in zama mai yawan la'anta ba; an aiko ni ne kawai don in zamanto rahama." [Muslim #2559].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ni rahama ce da aka yiwo kyauta da ita." [*As-Shari'ah* #1000 da *Almustadrak*, juzu'i na 1, shafi na 91, Dubi Al-Albani, *As-Silsilatus-Sahihah* #490].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya sanar da mutane cewa shi fa ana yi masa wahayi ne daga Allah cewa abin bautarsu na gaskiya Ɗaya ne kawai ba shi da wani abokin tarayya, don haka su miƙa wuya gare shi su yi imani da shi su kuma yi masa ɗa'a.
Sannan ya sanar da Manzonsa cewa, idan sun bijire masa sun ƙi karɓar abin da ya zo musu da shi na kaɗaita Allah da bauta masa shi kaɗai, to ya sanar da su cewa shi da su suna a kan wani al'amari iri ɗaya, na taware, watau ba shi ba su. Sannan kuma koyaushe suna matsa masa lamba da tambaya a kan sai ya sanar da su yaushe ne azabar Allah za ta sauko musu, kamar yadda Allah yake tsoratar da su? Sai Allah ya umarce shi ya faɗa musu cewa shi ma bai san yaushe ne wannan alƙawarin zai sauka ba, to amma dai su sani cewa duk maganganun da suke yi a bayyane ko a ɓoye Allah yana sane da su babu abin da yake ɓuya a gare shi kuma dukkansu sai ya saka musu a kan ayyukansu ɗaya bayan ɗaya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar Manzonsa da ya faɗa musu cewa shi kansa ba shi da wata masaniya game da jinkirta musu azaba da Allah ya yi. Mai yiwuwa ne kuma ya yi haka ne don ya zamo jarraba da talala a gare su, don kuma ya ba su damar jin daɗi na ɗan ƙanƙanin lokaci wanda Allah ya riga ya ƙaddara shi cikin iliminsa, domin su doge a kan kafirci da ɓata.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzon Allah (ﷺ) da ya yi addu'a, ya roƙi Allah Ubangijinsa da ya yi hukunci na gaskiya tsakaninsa da mutanensa waɗanda suka doge a kan kafircinsu, domin a wurin Allah Mai rahama ne kawai yake neman taimako bisa ga duk abin da suke faɗa kuma suke aikatawa na kafirci da ƙaryatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin yin tanadin kyawawan ayyuka domin zuwan ranar alƙiyama.

2. Tsananin abubuwan ban tsoro na ranar alƙiyama waɗanda za su sa mai shayarwa ta manta da abin da take shayarwa, mai ciki kuma ta yi ɓarin cikinta, hankulan mutane duk su ɓace.

3. Bayanin tsananin tausayin uwa ga ɗanta ƙarami, ta yadda ba za ta taɓa rabuwa da shi ba sai abu ya tsananta matuƙa.

22-Suratul Hajji

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ana kiran ta da sunan "*Suratul Hajji*" saboda an ambaci yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya shelanta wa mutane aikin hajji da kuma bayanin ayyukan da ake yi a wannan lokaci.

2. Sanda Aka Saurakar Da Ita:
Malamai sun yi saɓani wajen tantance inda aka saukar da wannan Sura:
• Wasu sun ce Sura ce *Makkiyya*, watau an saukar da ita ne gabanin hijira, in ban da ayoyi uku, watau daga aya ta 19 zuwa ta 22.
• Wasu kuma suka ce Sura ce *Madaniyya*, watau an saukar da ita ne bayan hijira zuwa Madina, in ban da ayoyi huɗu, watau daga aya ta 52 zuwa ta 55.
• Wasu kuma suka ce ayoyinta a gauraye suke, wasu *Makkiyya* ne wasu kuma *Madaniyya* ne ba tare da an tantance su ba. Malam Ibnu Aɗiyya ya fifita wannan ra'ayi a kan sauran.

3. Jerin Saukarta:
Wannan Sura ita ce ta ɗari da biyar (105) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *Suratun Nur* kafin *Suratul Munafikun*.

4. Adadin Ayoyinta:
A wajen mutanen Makka ayoyinta saba'in da bakwai ne (77). Amma a lissafin mutanen Sham adadinsu saba'in da huɗu ne (74). A wajen mutanen Basra kuwa adadinsu saba'in da biyar ne (75). A lissafin mutanen Kufa kuwa saba'in da takwas ne (78).

5. Babban Jigonta:
• Magana a kan girman Allah da miƙa wuya gare shi ta hanyar bijiro da abubuwa masu nuna cikakkiyar Kudurarsa da girmansa.
• Tabbatar da cewa Allah ne mai taimakon addininsa da manzanninsa da mabiyansu a duniya da lahira.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Magana a kan ranar alƙiyama da abubuwan ban tsoro da take cike da su.
• Kafa ƙwaƙƙwarar hujja a kan yiwuwar tashi bayan mutuwa.
• Sukan mushirikai a kan girman kansu na ƙin yarda da addinin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) na kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda suke tutiya da cewa su jikokinsa ne masu kare addininsa da kula da ɗakin da ya gina.
• Tunatar da mushrikai ni'imomin da Allah ya yi musu a cikin aikin hajji amma sai suka butulce masa.
• Kwatanta su da wasu al'ummu da Allah ya hallaka a baya domin sun bijire wa manzanninsa, don haka su ma hakan na iya samun su, saboda haka kada su ruɗu don ganin an jinkirta musu.

• Bayani a kan cewa ranar alƙiyama ita ce ranar hukunci tsakanin muminai da kafirai da bayyana wa kowanne matsayinsa da sakamakonsa.
• Bayanin girman sha'anin Alƙur'ani da kariyar da Allah yake ba shi daga Shaiɗan.
• Ba wa Musulmi izinin tashi tsaye su kare kansu daga ta'addancin kafirai da zaluncinsu.
• An rufe Surar da tunatar da Musulmi ni'imomin da Allah ya yi musu da zaɓin da ya yi wa wasu daga cikin mala'iku da mutane da taimakonsa ga muminai da kusanta su gare shi.

Suratul Hajji (1-2)

الٓرۚ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ وَقُرۡءَانٖ مُّبِينٖ ۝١ رُّبَمَا يَوَدُّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡ كَانُواْ مُسۡلِمِينَ ۝٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya ku mutane, ku kiyaye dokokin Ubangijinku. Lalle girgizar (ranar) alƙiyama abu ne mai girma.

2. Ranar da za ku gan ta, (don tsananin firgita) kowacce mai shayarwa za ta manta da abin da ta shayar, kuma kowacce mai ciki ta zubar da cikinta, ka ga kuma mutane suna tangaɗi, alhali kuwa ba bugaggu ba ne, sai dai azabar Allah ce mai tsanani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da kiran mutane gaba ɗaya ya umarce su da su kiyaye dokokin Ubangijinsu, su aikata abin da ya wajabta musu su kuma guji abin da ya hana su. Ya kuma tsoratar da su da cewa, ranar alƙiyama cike take da manya-manyan abubuwan ban tsoro. Daga cikinsu akwai wata babbar girgizar ƙasa mai tayar da hankali. Don haka wajibi ne mutane su yi tanadin kyawawan ayyuka domin zuwan wannan rana da ba ta da makawa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana yadda mutane za su ruɗe su ɗimauce sakamakon firgicin wannan ranar, domin kuwa saboda tsananin tsoro mace mai shayarwa za ta manta da jaririn da take shayarwa, sannan mai ciki za ta yi ɓarin cikinta, hankalin kowa duk ya ɓace su zamo kamar masu mayen giya, alhalin kuwa ba giya suka sha ba; tsananin azabar Allah ne kawai ya sanya su suka rasa hankulansu.

An karɓo daga Imran ɗan Husain (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wata rana a cikin ɗaya daga tafiye-tafiyen Manzon Allah (ﷺ) ya kula da cewa wasu sahabbansa sun yi wa sauran nisa sai ya ɗaga muryarsa ya karanta waɗannan ayoyi guda biyu. Yayin da sahabbansa suka ji haka sai suka ƙara sauri, suka kuma fahimci cewa yana so ne ya faɗa musu wata magana. Lokacin da suka taru a gabansa sai ya ce: "Shin ko kun san wacce rana ce waccan? (Watau wadda Allah yake magana a kanta cikin ayoyi biyu da ya karanta.)" Sai ya ce: "Ita ce ranar da Allah zai kirawo Adamu ya ce masa: "Ya kai Adamu, ka fito da waɗanda za a aika wuta." Sai ya ce: "Ya Ubangiji, su wane ne 'yan wuta?" Sai ya ce: "Daga cikin kowane dubu ka fitar da ɗari tara da tis'in da tara ka tura su zuwa wuta, ɗayan kuwa ka tura shi Aljanna." Sahabbai suna jin wannan magana sai duk suka ruɗe ba wanda aka gan shi ya yi dariya. Da Annabi (ﷺ) ya ga haka sai ya ce: "Ku yi aiki, kuma albishirinku! Na rantse da wanda raina yake a hannunsa, a tare da ku akwai wasu halittu guda biyu, a duk inda suke sai sun fi komai yawa, su ne Yajuju da Majuju da waɗanda suka hallaka daga cikin 'ya'yan Adamu da kuma 'ya'yan Iblis." Da jin haka sai hankalin sahabbai ya kwanta...." [Ahmad #19901 da Tirmizi #3169].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jayayya a addini ba tare da ilimi ba abu ne mai matuƙar muni.

2. Duk wanda ya bi hanyar Shaiɗan to babu makawa sai ya ɓatar da shi, kuma ƙarshensa shi ne shiga wutar Jahannama.

Suratul Hajji (3-4)

ذَرۡهُمۡ يَأۡكُلُواْ وَيَتَمَتَّعُواْ وَيُلۡهِهِمُ ٱلۡأَمَلُۖ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ٣ وَمَآ أَهۡلَكۡنَا مِن قَرۡيَةٍ إِلَّا وَلَهَا كِتَابٞ مَّعۡلُومٞ ٤

3. Daga mutane kuma akwai wanda yake jayayya game da Allah ba tare da wani ilimi ba, kuma yake bin kowanne shaiɗani mai tsaurin kai.

4. An ƙaddara masa (wato Shaiɗan) cewa duk wanda ya rungume shi to haƙiƙa zai ɓatar da shi kuma ya ja shi zuwa ga azaba ta (wutar) Sa’ira.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana mayar da martani ne ga waɗanda suke musanta tashi bayan mutuwa da zuwan ranar alƙiyama, da cewa a cikin mutane akwai wanda yake jayayya game da Kudurar Allah ba tare da wani ilimi ko wata hujja ba, har yana ganin wai Allah ba zai iya tayar da matattu bayan mutuwarsu ba. Ba wanda yake koyi da shi wajen riƙo da wannan mummunar aƙida in ban da duk wani shaiɗani mai tsaurin kai mai bijire wa Allah Ubangijinsa daga shaiɗanun aljannu ko na mutane shuwagabannin ɓata. Su waɗannan an riga an rubuta musu cewa duk wanda ya bi ɗaya daga cikinsu ya gaskata abin da yake saƙa masa a zuciya, to tabbas zai ɓatar da shi ne daga kan hanyar gaskiya, ya kuma ja shi zuwa ga azabar wuta, saboda ƙafirci da saɓon Allah da yake jan sa zuwa gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci ɗan’adam ta hanyar bin tsarin halitta daki-daki don ya nuna muhimmancin bin abu a sannu.

2. Halittar farko dalili ne a kan yiwuwar tashi bayan mutuwa.

3. Saukar ruwan sama a kan ƙasa har ta fito da tsirranta babban dalili ne a kan tashin halittu bayan mutuwa.

Suratul Hajji (5-7)

مَّا تَسۡبِقُ مِنۡ أُمَّةٍ أَجَلَهَا وَمَا يَسۡتَخِرُونَ ٥ وَقَالُواْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِي نُزِّلَ عَلَيۡهِ ٱلذِّكۡرُ إِنَّكَ لَمَجۡنُونٞ ٦ لَّوۡ مَا تَأۡتِينَا بِٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٧

5. Ya ku mutane, idan kun zamanto cikin kokwanton tashi (bayan mutuwa), to lalle Mu Muka halicce ku daga ƙasa, sannan daga maniyyi, sannan daga gudan jini, sannan daga tsoka, mai cikakkiyar halitta da kuma wadda ba cikakkiya ba, don Mu bayyana muku (Ikonmu). Kuma Muna tabbatar da abin da Muka ga dama a cikin mahaifa har zuwa wani lokaci ƙayyadajje, sannan kuma Mu fito da ku kuna jarirai, sannan kuma don ku kai cikar ƙarfinku; daga cikinku akwai wanda za a karɓi ransa, akwai kuma wanda za a bari har zuwa mafi ƙasƙantar rayuwa don ya kai ga halin da ba zai san komai ba bayan kuwa da can ya sani. Za ka kuma ga ƙasa a ƙeƙashe, sannan idan Muka saukar mata da ruwa sai ta girgiza ta kumbura kuma ta fitar da kowanne irin tsiro mai ƙayatarwa.

6. Wannan (kuwa) saboda lalle Allah Shi ne gaskiya, kuma lalle Shi ne Yake raya matattu, kuma lalle Mai iko ne a kan komai.

7. Kuma lalle alƙiyama za ta zo babu kokwanto game da ita, kuma lalle Allah zai tashi waɗanda suke cikin ƙaburbura.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da ƙarfafan dalilai biyu game da tashin matattu da aukuwar ranar alƙiyama.
Dalili na farko shi ne halittar ɗan'adam bayan a da babu shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne ya fari halittar Annabi Adamu uban mutane daga ƙasa, sannan ya halicci zurriyyarsa daga ruwan maniyyin namiji da na mace bayan ya shiga mahaifa. Daga maniyyi kuma ya koma daskararren jini, sannan ya zama tsokar nama wadda ba ta fi lomar mutum ba, sannan ta rikiɗa ta zama daidaitacciyar halitta ta mutum a cikin wannan mahaifar har zuwa lokacin haihuwa. Daga nan sai a haifi mutum mai rai, ko kuma wannan tsokar ta zama wata halitta wadda ba cikakken mutum ba, daga bisani a yi ɓarinsa. Allah ya bayyana cewa yana yin wannan ne duka domin ya ankarar da mutane cikakken ikonsa na halittar ɗan'adam zango bayan zango. Kuma shi yake da ikon raya jariran da ya ga damar raya su a cikin mahaifar iyayensu har zuwa lokacin haihuwarsu, watau cikin wata tara, sannan ya fitar da su 'yan ƙanana daga cikin cikkunan iyayensu mata. Su rayu bayan haka har ƙarfinsu ya kawo, hankalinsu kuma ya cika. To daga cikinsu akwai wanda zai mutu tun gabanin ya kai wannan lokacin, akwai kuma wanda zai yi tsawon rai har ya tsufa tukuf ƙarfinsa ya ƙare gaba ɗaya, hankalinsa ya yi rauni har ma wani lokaci ya fi yaro ƙarami taɓarɓarewa, ya manta da duk abin da a da ya sani.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle ana haɗa halittar ɗayanku a cikin cikin mahaifiyarsa, yana maniyyi kwana arba'in, sannan ya zama gudan jini kamar haka, sannan ya zama gudar tsoka kamar haka, sannan a aiko masa da mala'aika, a umarce shi da abubuwa guda huɗu: Ya rubuta aikinsa da arzikinsa da ajalinsa; ɗan wuta ne ko ɗan Aljanna. Sannan a umarce shi ya busa masa rai." [Bukhari #3205 da Muslim #2643].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance yana addu'a yana cewa: "Ya Allah, ina roƙon ka ka tsare ni daga rowa da kasala da tsufa da zama tsoho takwarkwasasshe da azabar ƙabari da fitinar Dujal da fitinar rayuwa da ta mutuwa." [Bukhari #4707].

Dalili na biyu shi ne raya ƙasa da ruwan sama bayan ƙeƙashewarta. Allah ya bayyana cewa za a ga ƙasa ta bushe babu wani tsiro a kanta, amma da zarar ruwan sama ya sauka a kanta sai a ga ta girgiza ta fitar da tsirranta, ta kumburo saboda tsirran da suka fito daga cikinta, ta fitar da kowane irin tsiro mai ban sha'awa da ƙayatarwa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗannan ƙarfafan dalilan biyu suna nuna abubuwa biyar:
Abu na farko, Allah shi ne abin bauta na gaskiya wanda babu shakka a cikin samuwarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai.
Na biyu, shi ne mai tayar da matattu bayan mutuwarsu kamar yadda ya halicce su a karon farko ya kuma raya ƙasa da ruwan sama bayan bushewarta.
Na uku, shi mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gagarar sa.
Na huɗu, tabbatar da zuwan ranar alƙiyama wadda babu wani kokwanto a kan zuwanta.
Na biyar, lalle Allah zai tayar da waɗanda suke cikin ƙaburbura domin yi musu hisabi a kan ayyukansu masu kyau da munana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hanyoyin samun shiriya su ne: Ko dai ilimi mai yin jagoranci zuwa ga sanin gaskiya, ko kuma wani mai shiryarwa wanda zai kama hannun mutum zuwa ga gaskiya, ko kuma wani amintaccen littafi ingantacce wanda zai nuna wa mutum gaskiya.

2. Girman kai rawanin tsiya ne wanda yake hana mai shi dacewa da gane gaskiya.

3. Yana daga cikin adalcin Allah kasancewarsa ba ya azabtar da wanda bai yi laifin komai ba.

Suratul Hajji (8-10)
مَا نُنَزِّلُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ إِلَّا بِٱلْحَقِّ وَمَا كَانُوٓاْ إِذًا مُّنظَرِينَ ﴿٨﴾ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا ٱلذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ﴿٩﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ فِى شِيَعِ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿١٠﴾

8. Daga mutane kuma akwai wanda yake jayayya game da (al'amarin) Allah ba tare da ilimi ba ko shiriya ko kuma wani littafi mai haske.

9. Yana juyar da kansa don ya ɓatar da (mutane) daga hanyar Allah; yana da wulaƙanci a duniya; kuma ranar alƙiyama Mu ɗanɗana masa azabar ƙuna.

10. (Za a ce da shi): "Wannan (kuwa) saboda abin da hannayenka suka aikata ne, kuma lalle Allah ba Mai zaluntar bayi ba ne."

Bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci waɗanda suka kauce hanyar shiriya saboda makauniyar biyayya ga wasu ɓatattu a aya ta 3, sai kuma a nan ya ambaci waɗanda su ne shugabannin ɓatan, da cewa, a cikin kafirai da akwai waɗanda suke yin jayayya game da Kaɗaitakar Allah ba tare da wani ilimi ba ko wata ingantacciyar hujja, ba kuma tare da bin wata shiriya ba da za ta shiryar da shi zuwa ga gaskiya, ba kuma tare da riƙo da wani littafi mai haske wanda Allah ya saukar domin shiriyarsu ba.
Allah ya bayyana mummunar ɗabi'ar wannan kafiri mai yawan jayayya, wanda yake karkatar da kansa domin girman kai da ƙoƙarin kautar da mutane daga yin imani da shiga addinin Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk mai irin wannan mummunan hali yana tare da ƙaskanci da wulaƙanci a nan duniya saboda Allah zai kunyata shi tun kafin ya je lahira. Sannan bayan ya je lahira Allah ya ɗanɗana masa azabar wuta mai tsananin ƙuna. Kuma a sanar da shi cewa wannan azabar da yake ɗanɗana saboda abin da ya aikata ne a duniya kuma Allah ba azzalumin kowa ba ne, domin ba wanda zai azabtar sai mai laifi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Riƙon addini lokacin yalwa da jin daɗi da kuma watsi da shi a lokacin tsanani da jarraba alama ce ta munafunci.

2. Duk wanda ya yi ridda ya saki addininsa to ya zama taɓaɓɓe asararre a nan duniya, domin ba zai taɓa samun abin da ya yi riddar saboda shi ba, kamar dukiya ko mulki ko ɗaukaka. Sannan asararsa ta lahira a bayyane take, domin ba zai samu shiga gidan Aljanna ba wadda faɗinta ya fi faɗin sammai da ƙasa, zai cancanci shiga wutar Jahannama ne ya kuma dawwama cikinta har abada.

3. Siffar duk wani abin bauta ba Allah ba ita ce bai mallaki amfani ko cutarwa ga kansa ba balle ga waninsa.

4. Manufar mai taimako ko aboki shi ne ya amfanar da mutum lokacin buƙatarsa, ya kuma kare shi daga wata cuta lokacin da ta nufo shi, idan ba zai iya yi masa ɗaya daga cikin biyun nan ba, to ba shi da wani amfani.

Suratul Hajji (11-13)

وَمَا يَأۡتِيهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ١١ كَذَٰلِكَ نَسۡلُكُهُۥ فِي قُلُوبِ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ١٢ لَا يُؤۡمِنُونَ بِهِۦ وَقَدۡ خَلَتۡ سُنَّةُ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٣

11. Daga mutane kuma akwai wanda yake bauta wa Allah a kan gaɓa; to idan alheri ya same shi sai ya nutsu da shi, idan kuwa wata masifa ta same shi sai ya juya a kan fuskarsa; to ya yi hasarar duniya da lahira. Wannan (kuwa) ita ce hasara bayyananniya.

12. Yana bauta wa wanin Allah, abin da ba zai cuce shi ba kuma ba zai amfane shi ba. Wannan kuwa shi ne ɓata mai nisa.

13. Yana bauta wa abin da cutarsa ta fi kusa fiye da amfaninsa. Tabbas mataimaki ya munana, kuma tabbas aboki ya munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halayyar wasu mutane waɗanda imani bai ratsa zukatansu ba, da cewa, a cikin mutane akwai wanda ya rasa alƙibla guda ɗaya, ya zamanto yana bautar Allah ne rabi da rabi, watau a cikin shakku. Idan ya yi imani ya ga yana samun alheri kamar wadata da ƙoshin lafiya da kwanciyar hankali, to sai ya ɗore a kan imaninsa da bautar Allah. Amma idan ya ga yana gamuwa ne da wata jarraba ta talauci ko rashin lafiya ko wani abu makamancin wannan, to sai ya riƙa ganin addininsa ne ya jawo masa haka. Don haka sai ya yi ridda ya koma kafirci. Allah ya bayyana cewa, tabbas wannan mutum ya yi asarar duniyarsa, domin kafircinsa ba zai ƙara masa wani abu a cikin rabonsa na duniya da aka riga aka rubuta masa ba, kuma ba zai yaye masa wata damuwar da yake ciki wadda Allah bai yi nufin yaye masa ita ba. Hakanan ya yi asarar lahirarsa, domin azabar Allah ce take jiran sa a can. Babu ko shakka wannan ita ce babbar asara a fili ƙarara.
Allah ya ci gaba da bayanin halin wannan mutum bayan ya yi ridda ya kafirce masa, da cewa zai ci gaba da kiran wasu ababen bauta ba Allah ba waɗanda ba za su iya cutar da shi komai ba, ba kuma za su amfane shi da komai ba. Wannan shi ne ɓata mai nisa tsakaninsa da gaskiya, domin ya kauce wa bautar wanda zai amfane shi ya kama wanda ba zai yi masa amfani ba. Hasali ma cutarwarsa gare shi ta fi zama tabbas a kan amfaninsa, wanda babu shi ma kwata-kwata.
Allah ya yi tir da wannan abin bauta ba Allah ba da sunan mataimaki ko aboki.

Suratul Hajji (14)

وَلَوۡ فَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَابٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فَظَلُّواْ فِيهِ يَعۡرُجُونَ ١٤

14. Lalle Allah Yana shigar da waɗanda suka yi imani kuma suka yi aiki na gari gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Lalle Allah Yana aikata abin da Ya ga dama.

Bayan Allah ya ambaci halin kafiri da mummunan sakamakonsa, sai kuma ya bayyana halin muminai da sakamakonsu, inda yake cewa, zai shigar da waɗanda suka yi imani kuma suka yi kyawawan ayyuka gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Ya tabbatar da cewa yana aikata abin da ya yi nufi,

don haka yana jin ƙan duk wanda ya nufi jin ƙansa, ya kuma azabtar da wanda ya nufi yi masa azaba, babu wanda ya isa ya hana shi.

Daga wannan ayar za mu fahimci cewa:

• Yin imani da aikata kyakkyawan aiki shi ne sanadiyyar shiga Aljanna.

Suratul Hajji (15-16)
مَن كَانَ يَظُنُّ أَن لَّن يَنصُرَهُ ٱللَّهُ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْـَٔاخِرَةِ فَلْيَمْدُدْ بِسَبَبٍ إِلَى ٱلسَّمَآءِ ثُمَّ لْيَقْطَعْ فَلْيَنظُرْ هَلْ يُذْهِبَنَّ كَيْدُهُۥ مَا يَغِيظُ ﴿١٥﴾ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلْنَٰهُ ءَايَٰتٍۭ بَيِّنَٰتٍ وَأَنَّ ٱللَّهَ يَهْدِى مَن يُرِيدُ ﴿١٦﴾

15. Wanda ya zamanto yana tsammanin cewa Allah ba zai taimake shi ba, (wato Annabinsa) a duniya da lahira, to sai ya hau sama da igiya, sannan ya yanke ta, ya duba shin wannan mugun tanadi nasa zai kawar da abin da yake cike da haushinsa?

16. Kamar haka kuwa Muka saukar da shi (Alƙur'ani) ayoyi mabayyana, kuma lalle Allah Yana shiryar da wanda Yake nufin (shiryar da shi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk wani mai tsammanin Allah ba zai taimaki Manzonsa (ﷺ) da addinin da ya zo da shi ba a duniya da lahira, yake kuma jiran ya ga addinin ya rushe, to ya sani wannan nasarar daga sama wurin Allah take sauka, don haka idan yana jin haushi to sai ya samu igiya ya kama ya hau sama sannan ya yanke igiyar ya faɗo ƙasa ya gani wannan zai kawar masa haushinsa? Allah dai zai ci gaba da taimakon Manzonsa da addininsa ko mutum yana so ko ba ya so.
Sannan Allah ya bayyana cewa kamar yadda ya bayyana hujjoji a kan tashin matattu da kuma tashin alƙiyama, to haka ya saukar wa Annabi Muhammadu (ﷺ) Alƙur'ani wanda ya ƙunshi ayoyi bayyanannu, kuma yana shiryar da wanda ya ga damar shiriyarsa ya nuna masa gaskiya ya kuma ba shi ikon bin ta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah mai taimakon addininsa ne kafirai sun ƙi ko sun so.

2. Cire wa kafirai ƙauna daga samun nasarar karya addinin Allah da kuma albishir ga muminai da samun nasara daga Allah.

3. Shiriya a hannun Allah take, shi yake shiryar da wanda ya ga dama.

Suratul Hajji (17)
إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَٱلَّذِينَ هَادُوا۟ وَٱلصَّٰبِـُٔونَ وَٱلنَّصَٰرَىٰ وَٱلْمَجُوسَ وَٱلَّذِينَ أَشْرَكُوٓا۟ إِنَّ ٱللَّهَ يَفْصِلُ بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ شَهِيدٌ ﴿١٧﴾

17. Lalle waɗanda suka yi imani da waɗanda suka zama Yahudawa da Sabi'awa da waɗanda suka zama Majusawa da kuma waɗanda suka yi shirka, lalle Allah zai yi hukunci a tsakaninsu ranar alƙiyama. Lalle Allah Mai ganin kowane abu ne.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lalle waɗanda suka yi imani daga al'ummar Musulmi da kuma Yahudawa da Sabi'awa da Nasara da Majusawa masu bautar wuta da masu shirka, duk gaba ɗayansu Allah zai yi musu hukunci a ranar alƙiyama ya shigar da muminai gidan Aljanna ya kuma shigar da sauran wuta. Lalle Allah yana ganin duk ayyukan bayinsa da maganganunsu, babu abin da yake ɓuya daga gare shi kuma zai yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa. (Dubi *Suratul Baƙara,* aya ta 62).

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah zai yi hukunci da adalci a ranar alƙiyama a tsakanin dukkan mabiya addinai; waɗanda suka yi imani da shi da manzanninsa ya saka su gidan Aljanna, waɗanda kuwa suka kafirce masa suka ƙaryata manzanninsa ya jefa su wutar Jahannama.

2. Allah Mai ganin ayyukan bayinsa ne gaba ɗaya kuma zai yi musu hisabi a kai.

Suratul Hajji (18)

أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يَسۡجُدُ لَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ وَٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُ وَٱلنُّجُومُ وَٱلۡجِبَالُ وَٱلشَّجَرُ وَٱلدَّوَآبُّ وَكَثِيرٞ مِّنَ ٱلنَّاسِۖ وَكَثِيرٌ حَقَّ عَلَيۡهِ ٱلۡعَذَابُۗ وَمَن يُهِنِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن مُّكۡرِمٍۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَفۡعَلُ مَا يَشَآءُ ١٨

18. Shin ba ka san cewa duk abin da yake cikin sammai da ƙasa suna yin sujjada ne ga Allah ba, (haka ma) rana da wata da taurari da duwatsu da bishiyoyi da dabbobi da kuma mutane masu yawa; da yawa kuma azaba ta tabbata a kansu? Duk kuwa wanda Allah Ya wulaƙanta, to ba shi da wani mai girmama shi. Lalle Allah Yana aikata abin da Ya ga dama.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Manzonsa cewa ɗaukacin mala'ikun da suke cikin sammai da muminai mutane da aljannu da suke bayan ƙasa suna yi masa sujjada domin ɗa'a a gare shi. Hakanan rana da wata da taurari a sama da duwatsu da bishiyoyi da dabbobi a ƙasa gaba ɗayansu suna yi masa sujjadar miƙa wuya gare shi. Haka kuma mutane masu yawa a bayan ƙasa suna yi masa sujjadar ɗa'a, da yawa kuma sun ƙi su yi masa sujjada, don haka azabarsa ta tabbata a kansu saboda kafircinsu. Duk kuma wanda Allah ya hukunta masa ƙaskanci da wulaƙanci saboda kafircinsa to babu wanda ya isa ya girmama shi. Allah kuma yana aikata abin da ya ga dama ne babu mai tilasta shi.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya tambaye ni ya ce: "Shin ka san inda wannan ranar take tafiya?" Sai na ce: "Allah da Manzonsa ne suka fi sani." Sai ya ce: "To lalle tana tafiya ne ta yi sujjada a ƙarƙashin Al'arshi, sannan ta nemi izinin sake fitowa. To lokaci ya kusa zuwa da za a ce mata: 'Ki koma ta inda kika zo'." [Bukhari #3199 da Muslim #159].

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai, duba da yadda manya-manyan halittun sammai da na ƙasa suke rusuna masa tare da miƙa wuya a gare shi da kuma gudanarsu a bisa umarninsa.

2. Tabbatar da cewa sauran halittun Allah ban da mutum da aljani da mala'iku su ma suna yi wa Allah sujjada kowanne gwargwadon yadda ya dace da shi.

3. Duk wanda Allah ya wulaƙantar da shi saboda kafircinsa da saɓon Allah, to duk duniya babu mai iya ɗaga matsayinsa da martabarsa. Don haka duk mai neman ɗaukaka to ya neme ta wajen Allah ta hanyar yi masa ɗa'a da bin umarnin Manzonsa da kauce wa abin da ya hana.

Suratul Hajji (19-24)

*هَٰذَانِ خَصۡمَانِ ٱخۡتَصَمُواْ فِي رَبِّهِمۡۖ فَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ قُطِّعَتۡ لَهُمۡ ثِيَابٞ مِّن نَّارٖ يُصَبُّ مِن فَوۡقِ رُءُوسِهِمُ ٱلۡحَمِيمُ ١٩ يُصۡهَرُ بِهِۦ مَا فِي بُطُونِهِمۡ وَٱلۡجُلُودُ ٢٠ وَلَهُم مَّقَٰمِعُ مِنۡ حَدِيدٖ ٢١ كُلَّمَآ أَرَادُوٓاْ أَن يَخۡرُجُواْ مِنۡهَا مِنۡ غَمٍّ أُعِيدُواْ فِيهَا وَذُوقُواْ عَذَابَ ٱلۡحَرِيقِ ٢٢ إِنَّ ٱللَّهَ يُدۡخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ يُحَلَّوۡنَ فِيهَا مِنۡ أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٖ وَلُؤۡلُؤٗاۖ وَلِبَاسُهُمۡ فِيهَا حَرِيرٞ ٢٣ وَهُدُوٓاْ إِلَى ٱلطَّيِّبِ مِنَ ٱلۡقَوۡلِ وَهُدُوٓاْ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلۡحَمِيدِ ٢٤

19. Biyu ɗin nan (muminai da kafirai) masu jayayya ne da suka yi jayayya game da Ubangijinsu (wato addininsu); waɗanda suka kafirce sai aka ɗinka musu tufafi na wuta, kuma ana zuba musu tafasasshen ruwa ta saman kawunansu.

20. Ana narka abin da yake cikinsu da shi (tafasasshen ruwan) da kuma fatu.

21. Suna kuma (shan duka) da gudumomi na baƙin ƙarfe.

22. Duk sanda suka yi nufin fita daga cikinta (wutar) saboda baƙin ciki sai a sake mayar da su cikinta, (a ce da su): "Ku ɗanɗani azabar gobara."

23. Lalle Allah Yana shigar da waɗanda suka yi imani kuma suka yi ayyuka na gari gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, ana yi musu ado a cikinsu da awarwaro na zinare da kuma lu'ulu'u; tufafinsu kuwa a cikinsu alharini ne.

24. Kuma an shiryar da su zuwa ga magana mai daɗi (a duniya, wato Kalmar Shahada), an kuma shiryar da su zuwa ga tafarkin (Allah) Sha-yabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana makomar ƙungiyoyi guda biyu, watau muminai da suka yi aiki da dokokinsa, da kuma waɗanda suka kafirce masa suka bijire wa manzanninsa. Waɗannan ƙungiyoyi biyu suna jayayya ne game da Ubangiji, ƙungiyar kafirai za su gamu da matsananciyar azaba domin kuwa za a ɗinka musu tufafi na wuta waɗanda za su rufe jikinsu ta ko'ina, a kuma riƙa kwararo musu da tafasasshen ruwa ta saman kawunansu, wanda da shi ne za a riƙa narka kayan cikinsu, da fatunsu ya sa duk su zagwanye. Bugu da ƙari kuma mala'iku za su yi ta dukan su a kawunansu da gudumomi na baƙin ƙarfe. Duk kuma sa'adda suka yi yunƙurin fitowa daga cikin wannan matsananciyar azaba sai a mayar da su cikinta, a ce da su: "Ku ɗanɗani azabar gobara."

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) , ya kasance yana rantsuwa da Allah cewa wannan aya ta 19 ta sauka ne game da Hamza da abokansa su biyu, da Utba da abokansa su biyu, ranar da suka yi fito-na-fito a yaƙin Badar. [Bukhari #3966 da Muslim #3033].

An karɓo daga Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Ni ne farkon wanda zai gurfana a gaban Allah mai rahama domin husuma a ranar alƙiyama." Kaisu ya ce: A kansu wannan ayar ta sauka: (Waɗannan biyun su ne suka yi jayayya game da Ubangijinsu). Ya ce: "Su ne waɗanda suka yi fito-na-fito a ranar yaƙin Badar,

watau su ne: Aliyyu da Hamza da Ubaida (ɓangaren muminai) da Shaibatu ɗan Rabi'a da Utbatu ɗan Rabi'a da Alwalidu ɗan Utbatu (ɓangaren kafirai)." [Bukhari #4744].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci sakamakon ƙungiyar muminai, da cewa waɗannan su ne waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki na ƙwarai, to su Allah zai shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Ana kuma yi musu ado da awarwaro na zinare da lu'u-lu'u, sannan kuma tufafinsu na sawa na alhariri ne.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa tun suna duniya ya shiryar da su game da faɗar daddaɗar magana, ita ce Kalmar Shahada da kabbara da kirari ga Allah, kuma ya shiryar da su zuwa ga hanyar Musulunci abin yabo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin cewa 'yan wuta ma suna da nasu tufafi na sawa, sai dai ba na ado ba ne ko na suturce al'aura; waɗannan tufafi ne na musamman na wuta waɗanda za a sanya musu a jikinsu don a ninninka musu azaba.

2. Bayanin cewa azabar 'yan wuta ba ta taƙaita ga gangar jiki ba kawai; ta shafi har da ruhi.

3. Kafiri abokin rigimar mumini ne shi ma mumini haka, a kowanne wuri kuma a kowanne zamani.

4. Tabbatar da aƙidar tashi bayan mutuwa da abin da zai biyo baya na sakamako bisa ayyukan bayi.

Suratul Hajji (25)
إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِ ٱلَّذِي جَعَلۡنَٰهُ لِلنَّاسِ سَوَآءً ٱلۡعَٰكِفُ فِيهِ وَٱلۡبَادِۚ وَمَن يُرِدۡ فِيهِ بِإِلۡحَادِۭ بِظُلۡمٖ نُّذِقۡهُ مِنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ ٢٥

25. Lalle waɗanda suka kafirta suke kuma toshe hanyar Allah da kuma Masallacin Harami wanda Muka sanya shi bai-ɗaya ga mutane, mazaunin cikinsa da kuma mai zuwa (daga waje). Wanda kuwa ya nufe shi da wata fanɗara da zalunci to za Mu ɗanɗana masa azaba mai raɗaɗi.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan halin da mushirikai suke ciki na kafirce wa Allah da hana mutane karɓar addinin Musulunci, da kuma kange su daga shiga Masallaci mai alfarma na Makka, kamar yadda suka hana Manzon Allah da sahabbansa yayin da suka je don yin Umra a shekarar Hudaibiyya, watau shekara ta shida bayan hijira. Waɗannan kafirai za su gamu da azabar Allah mai tsanani idan har suka mutu ba su tuba ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ya sanya wannan Masallacin na Harami ya zamanto alƙibla ce ga dukkan Musulmi lokacin sallolinsu a duk inda suke, kuma wuri ne na yin aikin Hajji da Umara. Kuma mazaunin garin Makka da baƙo wanda ya zo daga wajenta duka ɗaya suke a cikin wannan Haramin, babu wanda zai nuna ya fi wani haƙƙi a cikinsa. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kashedi ga duk wani wanda zuciyarsa za ta riya masa yin wani aikin assha a cikinsa na zalunci ko na saɓon Allah, to lalle Allah zai ɗanɗana masa azaba mai raɗaɗi.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman darajar Masallaci mai alfarma na Makka da munin laifin hana mutane isa gare shi domin bautar Allah. Allah ya tanade shi ne don duk wani mai bautar sa mai kaɗaita shi, don haka bai halatta wani ya hana masu zuwa bautar Allah isa gare shi ba. Kuma babu wanda ya fi wani haƙƙi a cikinsa.

2. Girman lamarin Haramin Makka; saboda ƙudure niyyar aikata wani zalunci ko wani saɓon Allah a cikinsa kawai ya isa ya jawo wa mutum azabar Allah ko da kuwa bai aikata ba, to ina kuma ga wanda har ya kai ga aikatawa?

3. Kamar yadda ake ninninka lada a wasu lokuta da wurare masu daraja, to hakanan ma ake ninninka zunubi a cikinsu.

Suratul Hajji (26-29)
وَإِذۡ بَوَّأۡنَا لِإِبۡرَٰهِيمَ مَكَانَ ٱلۡبَيۡتِ أَن لَّا تُشۡرِكۡ بِي شَيۡـٔٗا وَطَهِّرۡ بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡقَآئِمِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ ٢٦ وَأَذِّن فِي ٱلنَّاسِ بِٱلۡحَجِّ يَأۡتُوكَ رِجَالٗا وَعَلَىٰ كُلِّ ضَامِرٖ يَأۡتِينَ مِن كُلِّ فَجٍّ عَمِيقٖ ٢٧ لِّيَشۡهَدُواْ مَنَٰفِعَ لَهُمۡ وَيَذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ فِيٓ أَيَّامٖ مَّعۡلُومَٰتٍ عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلۡأَنۡعَٰمِۖ فَكُلُواْ مِنۡهَا وَأَطۡعِمُواْ ٱلۡبَآئِسَ ٱلۡفَقِيرَ ٢٨ ثُمَّ لۡيَقۡضُواْ تَفَثَهُمۡ وَلۡيُوفُواْ نُذُورَهُمۡ وَلۡيَطَّوَّفُواْ بِٱلۡبَيۡتِ ٱلۡعَتِيقِ ٢٩

26. Kuma (ka tuna) lokacin da Muka nuna wa Ibrahimu gurbin Ɗakin (Ka’aba, Muka ce da shi): “Kada ka haɗa komai da Ni (wajen bauta), kuma ka tsarkake Ɗakina ga masu ɗawafi da masu zama a cikinsa da kuma masu ruku’i masu sujjada.

27. Kuma ka yi shela cikin mutane saboda yin Hajji, za su zo maka matafiya a ƙasa da kuma kan kowanne raƙumi mai ɗamammen ciki, za su zo maka daga kowane lungu mai nisa.

28. Don su halarci amfanin da za su samu, kuma su ambaci sunan Allah cikin kwanaki sanannu a kan abin da Muka arzuta su da shi na dabbobin ni’ima (watau raƙuma da tumaki da awakai da shanu); sai ku ci daga gare su kuma ku ciyar da galaɓaitaccen matalauci.

29. Sannan su gusar da ƙazantarsu (kamar yin aski da yanke farce), kuma su cika alƙawarinsu (na yin hadaya da layya), kuma su yi ɗawafi a 'yantaccen Ɗaki (na Ka’aba).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman darajar Ɗakinsa mai alfarma da kuma darajar wanda ya gina shi, watau Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya umarci Annabi (ﷺ) ya tuna lokacin da ya nuna wa Annabi Ibrahimu gurbin Ɗakin Ka’aba da iyakokinsa wanda a da bai taɓa saninsa ba. Ya kuma yi masa wahayi da cewa kada ya yi shirka wajen bautar Allah, ya bauta wa Allah shi kaɗai, ya kuma tsarkake Ɗakinsa daga dukkan najasa ta zahiri da ta baɗini domin amfanin masu ɗawafi da masallata a cikinsa.
Ya kuma umarci Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya yi shela a cikin mutane ya kira su zuwa ga wannan Ɗakin domin aikin Hajji, Allah ya tabbatar masa da cewa mutane za su riƙa yin tururuwa zuwa gare shi, wasu a ƙafa wasu haye a kan ramammun raƙuma saboda wahalar tafiya, za su ɗauko su da guzirinsu daga kowace hanya mai nisa. Za su zo domin su halarci abubuwa masu yawa da za su amfane su, kamar samun gafarar Allah da gwaggwaɓan lada da haɗin kai tsakanin muminai da makamantansu. Kuma domin su ambaci sunan Allah lokacin da za su yanka dabbobin hadayarsu, ta raƙuma da shanu da tumaki a cikin kwanakin yanka na aikin Hajji, watau ranar goma ga watan Zulhijja da kwana uku bayansa. Duk

wannan domin su nuna godiyarsu ga Allah da ya arzuta su da waɗannan dabbobi. Allah kuma ya umarce su da su ci daga naman hadayarsu su kuma ciyar da mabuƙata da matalauta daga ciki.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jingina Ɗakin Ka'aba zuwa ga sunan Allah yana nuna girman darajarsa da falalarsa, yana kuma ƙara danƙon ƙaunarsa a cikin zukata, da kuma nuna muhimmancin tsarkake shi da tsaftace shi daga duk wata ƙazanta domin masu ɗawafi da salla a cikinsa.

2. Falalar Tauhidi, domin shi ne babban maƙasudin gina Ɗakin Allah da raya shi. Duk sauran ibadu suna biye ne da Tauhidi.

3. An fara ambaton ɗawafi sannan I'itikafi sai kuma salla, domin babu inda ake yin ɗawafi sai a nan, shi kuma I'itikafi ba a yin sa sai a masallatai, saɓanin salla wadda ita ana yin ta a duk inda ta kama.

4. Muhimmancin tuna wa mutane ibadar aikin Hajji musamman ga wanda ya jahilce ta, domin masu zuwa wannan Ɗakin su yawaita a kowace shekara.

5. Tafiya aikin Hajji a ƙafa ko a kan abin hawa. Duk wanda zai fi inganta aikin hajinsa yayin da ya yi shi a kan abin hawa, to yin sa a hakan ya fi falala. Wanda kuwa zai fi kyautata shi idan ya yi shi a ƙafa, to yin sa a ƙasa gare shi ya fi lada. Don haka ba a fifita ɗaya a kan ɗaya ta kowace fuska.

6. Aikin Hajji yana cike da amfani mai yawa ta fuskar addini da rayuwa. Ta fuskar addini mutum zai sami lada mai yawa ta hanyar tsantsanta bautarsa ga Allah da kuma ayyukan ibada da samun kankarewar zunubbai. Ta fuskar rayuwa kuwa ta hanyar kasuwanci da kai wa mazauna wannan gari mai albarka abubuwan da suke buƙata na rayuwa da ciyar da mabuƙata.

7. Dasa aƙidar Tauhidi a cikin zukata ta hanyar ganin Ɗakin da aka gina shi domin Tauhidi ido-da-ido, domin mutane sun fi tasirantuwa da abin da suka gani fiye da abin da suka ji labarinsa kawai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wasu kwanaki da aikin ƙwarai ya fi falala a cikinsu kamar waɗannan kwanakin (goma na farkon Zulhijja)." Sahabbai suka ce: "Har ma da jihadi?" Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Har ma da jihadi, sai dai mutumin da ya fita yaƙi da ransa da dukiyarsa bai kuma dawo da komai ba." [Bukhari #969 da Ahmad #1968].

An karɓo daga Abu Ƙatada (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Manzon Allah (ﷺ) game da azumin ranar Arfa sai ya ce: "Ina tsammanin zai kankare zunubin shekara mai wucewa da mai zuwa." [Muslim #1162].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mahajjata da su kammala ayyukansu na Hajji su yi aski da yanke farce da kawar da duk wata ƙazanta daga jikinsu su cire haraminsu. Ya kuma umarce su da su cika alƙawarin da suka ɗaukar wa kansu na bakance da yin Hajji ko Umara ko hadaya, su kuma yi ɗawafin a Ɗakin da Allah ya 'yanta shi daga duk wani azzalumi tun lokacin da aka gina shi.

Suratul Hajji (30-33)

ذَٰلِكَۖ وَمَن يُعَظِّمۡ حُرُمَٰتِ ٱللَّهِ فَهُوَ خَيۡرٞ لَّهُۥ عِندَ رَبِّهِۦۗ وَأُحِلَّتۡ لَكُمُ ٱلۡأَنۡعَٰمُ إِلَّا مَا يُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡۖ فَٱجۡتَنِبُواْ ٱلرِّجۡسَ مِنَ ٱلۡأَوۡثَٰنِ وَٱجۡتَنِبُواْ قَوۡلَ ٱلزُّورِ ٣٠ حُنَفَآءَ لِلَّهِ غَيۡرَ مُشۡرِكِينَ بِهِۦۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَكَأَنَّمَا خَرَّ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَتَخۡطَفُهُ ٱلطَّيۡرُ أَوۡ تَهۡوِي بِهِ ٱلرِّيحُ فِي مَكَانٖ سَحِيقٖ ٣١ ذَٰلِكَۖ وَمَن يُعَظِّمۡ شَعَٰٓئِرَ ٱللَّهِ فَإِنَّهَا مِن تَقۡوَى ٱلۡقُلُوبِ ٣٢ لَكُمۡ فِيهَا مَنَٰفِعُ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى ثُمَّ مَحِلُّهَآ إِلَى ٱلۡبَيۡتِ ٱلۡعَتِيقِ ٣٣

30. Wannan (umarni da aka yi muku) kuwa, duk wanda ya girmama abubuwan da Allah Ya hana (a Hajji) to shi ya fi masa alheri a wurin Ubangijinsa. An kuma halatta muku dabbobin ni'ima, in ban da waɗanda aka karanta muku (haramcinsu). To sai ku nisanci ƙazanta ta bauta wa gumaka, kuma ku nisanci faɗar shaidar zur.

31. Kuna masu kauce wa ɓarna don Allah, ba masu haɗa shi da wasu ba. Duk wanda kuwa ya haɗa Allah da wani, to kamar ya faɗo ne daga sama, sai tsuntsaye suka fauce shi, (suka yagalgala shi) ko kuma iska ta jefa shi cikin wani wuri mai zurfi (ta rugurguza shi).

32. Wannan kuwa (haka yake), duk wanda ya girmama wuraren ibadar (Hajji) na Allah to lalle wannan yana daga taƙawar zukata.

33. Kuna da wata moriya game da su (dabbobin) har zuwa wani lokaci ƙayyadajje (shi ne lokacin yanka su), sannan kuma wurin yankansu zuwa ga Ɗaki ne 'yantacce (wato Harami baki ɗayansa).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa hukunce-hukunce na aikin Hajji da suka gabata abubuwa ne da ya yi umarni da su ya kuma wajabta su ga muminai, don haka lalle su girmama abin da ya wajabta musu. Allah ya bayyana cewa duk wanda ya nisanci abin da aka hana mai ihrami aikatawa domin girmama iyakokin Allah da kauce wa keta su da kuma kiyaye alfarmar abubuwa masu alfarma, to wannan shi ya fi musa alheri a wajen Ubangijinsa duniya da lahira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar wa da mutane cewa ya halatta musu cin naman dabbobin ni'ima, watau raƙuma da shanu da tumaki, babu wani nau'i nasu da aka haramta cin namansu ko amfani da su, kamar yadda mushirikan Larabawa suka riƙa yi a Jahiliyya. Idan ma akwai, to sai fa abin da Allah ya bayyana haramcinsa a wasu ayoyin Alƙur'ani, kamar mushe da jini mai kwarara da makamantansu, kamar yadda ya zo a cikin *Suratul Ma'ida,* aya ta 3.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni ga mutane da su nisanci duk wata ƙazanta ta gumaka da duk wata maganar ƙarya ga Allah ko ga wani daga cikin bayinsa.

An karɓo daga Abu Bakra (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Shin ba na faɗa muku mafi girman zunubi ba?" Sahabbai suka ce: "E, a faɗa mana ya Ma'aikin Allah." Sai ya ce: "Shirka da Allah da saɓa wa iyaye." Yana kishingiɗe sai ya tashi zaune ya ce: "Ku saurara, da maganar ƙarya, ku saurara, da shaidar zur." Annabi ya yi ta maimaita wannan maganar har sai da sahabbai suka ce ina ma ya yi shiru. [Bukhari #2654 da Muslim #87].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su tsarkake ibadarsu gare shi shi kaɗai su kauce wa duk wani addini ba Musulunci ba, kada kuma su haɗa komai da shi wajen bauta. Ya kamanta duk wanda ya haɗa Allah da wani cikin bauta, da cewa ya yi kama da wanda ya faɗo daga sama, ko dai tsuntsaye su fauce shi su yagalgala namansa da ƙasusuwansa, ko kuma iska ta jefa shi cikin wani rami mai zurfi inda zai kakkarye ya hallaka.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk waɗannan abubuwa da ya yi umarni da su na kaɗaita shi da tsantsanta bauta gare shi da nisantar gumaka da maganar ƙarya, duk suna cikin dokokin da

ya wajabta wa Musulmi su kiyaye su. Kma duk wanda ya girmama alamomin addini, kamar hadaya da sauran ayyukan Hajji, to wannan alama ce ta taƙawar zukata.
Ya bayyana cewa cikin hadayar da mahajjata suke yankawa yayin gama aikin hajjinsu akwai wasu abubuwa masu amfani gare su, kamar hawansu da amfani da gashinsu da nononsu da sauransu har zuwa lokacin yankansu yayin da suka iso Ɗakin Allah mai dogon tarihi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin cewa babbar manufar aikin Hajji ita ce tabbatar da Tauhidi da watsar da shirka.

2. Munin laifin shaidar zur har ta kai Allah yana haɗa shi da shirka.

3. Kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ba da lada ga wanda ya yi kyakkyawan aiki, hakanan yake ba da lada ga wanda ya guje wa abin da ya haramta.
4. Ma’anar taƙawar zukata ita ce bautar Allah shi kaɗai da cikakkiyar soyayya da ƙanƙantar da kai ga Allah. Wannan ita ce hanyar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan al'ummun da suka gabaci wannan al’umma ta Musulmi Allah ya tsara musu hanyar da za su kusance shi da ita, ta hanyar yanka dabbobi domin samun lada a kai.

2. Allah ya shar’anta yanka na hadaya ko na layya ko na wata ibada ta neman kusanci da shi domin yawan ambaton sunansa lokacin yanka da godiya ga ni’imominsa masu yawa.

3. Falalar ambaton Allah, watau zikiri.

4. Yanka ana yin sa ne domin neman kusanci ga Allah shi kaɗai. Ba ya halatta a yi yanka don neman kusanci ga wani mahaluƙi kowane ne shi.

5. Falalar ƙasƙantar da kai ga Allah da ikhlasi wajen bauta, tare da ambaton siffofinsu.

6. Zikirin Allah yana ƙara sanya wa zuciya tsoron Allah.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai wajabta wa bawansa ciyar da dukiyarsa gaba ɗaya ba; ya umarce shi ne da ya ciyar da wani kaso kaɗan daga cikinta, don zartar da wannan umarni ya zamo mai sauƙi ga duk wanda Allah ya hore masa dukiya ba don ƙarfinsa ko dabararsa ba.

Suratul Hajji (34-35)
وَلِكُلِّ أُمَّةٖ جَعَلۡنَا مَنسَكٗا لِّيَذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ عَلَىٰ مَا رَزَقَهُم مِّنۢ بَهِيمَةِ ٱلۡأَنۡعَٰمِۗ فَإِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞ فَلَهُۥٓ أَسۡلِمُواْۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُخۡبِتِينَ ٣٤ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتۡ قُلُوبُهُمۡ وَٱلصَّٰبِرِينَ عَلَىٰ مَآ أَصَابَهُمۡ وَٱلۡمُقِيمِي ٱلصَّلَوٰةِ وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ٣٥

34. Kowacce al’umma kuma Mun sanya musu (irin) bautar (da za su yi) don su ambaci sunan Allah bisa abin da Ya arzuta su da shi na dabbobin ni’ima. Sannan abin bautarku abin bauta ne guda Ɗaya, to gare Shi kawai za ku miƙa wuya. Kuma ka yi albishir ga masu ƙasƙantar da kai.

35. (Su ne kuwa) waɗanda, idan aka ambaci Allah sai zukatansu su raurawa, kuma masu haƙuri bisa abin da ya same su, kuma masu tsai da salla, kuma masu ciyarwa daga abin da Allah Ya arzuta su (da shi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kowace al'umma da ta gabata ya tanadar mata hanyar da za ta bauta masa ta hanyar zubar da jinin abin yanka domin neman kusanci gare shi. Kuma ambaton sunan Allah lokacin da za su yanka abin da za su kusanci Allah da yankansa. Yin haka ya zama godiya ne ga Allah bisa ga abin da ya arzuta su da shi na dabbobin ni'ima, watau raƙuma da shanu da tumaki.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya yi layya da raguna biyu masu launin baƙi-baƙi, sai na ga ya danne wuyansu da ƙafarsa ya yi Bismilla ya yi kabbara ya yanka su da hannunsa." [Bukhari #5558 da Muslim #1966].

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na halarci sallar layya tare da Annabi (ﷺ) a filin idi, lokacin da ya gama huɗubarsa ya sauko daga kan minbari sai aka zo masa da rago sai ya yanka shi da hannunsa, ya ce: "*Bismillahi Wallahu Akbar*, wannan nawa ne da kuma wanda bai sami damar yin layya ba daga cikin al'ummata." [Abu Dawud #2810 da Tirmizi #1521].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da mutane cewa abin bautarsu Ɗaya ne ba shi da abokin tarayya, don haka su miƙa wuya a gare shi su yi masa biyayya. Ya kuma umarci Manzon Allah (ﷺ) cewa ya yi albishir ga masu ƙasƙantar da kai ga Allah da ikhlasi, ya kuma faɗa musu abin da zai faranta musu rai.
Sai ya bayyana wasu siffofi huɗu na masu ƙasƙantar da kansu ga Allah:
Siffa ta farko, su ne waɗanda idan an ambaci Allah sai zukatansu su raurawa saboda tsoron uƙubarsa.
Ta biyu, su ne masu haƙuri a kan duk abin da ya same su marar daɗi, watau ba sa raki ko nuna hushi game da ƙaddarar Allah.
Ta uku, su ne masu tsayar da salla yadda aka umarce su da kula da lokutanta da rukunanta da wajibanta da mustahabbanta.
Ta huɗu, su ne masu ciyarwa daga dukiyar da Allah ya arzuta su da ita; ciyarwa ta wajibi kamar zakka da ta sadaka da sauran ayyukan alheri.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tausaya wa mabuƙata da taimaka musu wata hanya ce ta godiya ga Allah.

2. Sarrafa dabbobi da amfanuwa da su horewa ce daga Allah ga ɗan'adam domin ya yi masa godiya a kai.

3. Yawan ayyukan ɗan'adam ba shi ne babban abin la'akari a wurin Allah ba. Babban abin la'akari a wurinsa shi ne ikhlasi, watau tsantsanta bautar gare shi.

4. Shiriyar Allah ga bawa ita ce mafi girman ni'imarsa gare shi, don haka ya wajaba bawa ya zamanto mai godiya ga Allah a kanta koyaushe.

Suratul Hajji (36-37)

وَٱلۡبُدۡنَ جَعَلۡنَٰهَا لَكُم مِّن شَعَٰٓئِرِ ٱللَّهِ لَكُمۡ فِيهَا خَيۡرٞۖ فَٱذۡكُرُواْ ٱسۡمَ ٱللَّهِ عَلَيۡهَا صَوَآفَّۖ فَإِذَا وَجَبَتۡ جُنُوبُهَا فَكُلُواْ مِنۡهَا وَأَطۡعِمُواْ ٱلۡقَانِعَ وَٱلۡمُعۡتَرَّۚ كَذَٰلِكَ سَخَّرۡنَٰهَا لَكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ٣٦ لَن يَنَالَ ٱللَّهَ لُحُومُهَا وَلَا دِمَآؤُهَا وَلَٰكِن يَنَالُهُ ٱلتَّقۡوَىٰ مِنكُمۡۚ كَذَٰلِكَ سَخَّرَهَا لَكُمۡ لِتُكَبِّرُواْ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمۡۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُحۡسِنِينَ٣٧

36. (Rakuma) kuma masu ƙiba Mun sanya muku su alamomi ne na bautar Allah; kuna da amfani game da su (na rayuwarku). To sai ku ambaci sunan Allah a kansu suna tsaye a kan ƙafa uku (lokacin soke su). To idan ransu ya fita bayan sun faɗi, sai ku ci daga gare su kuma ku ciyar da mai wadatar zuci da kuma mai bara. Kamar haka Muka hore muku su don ku yi godiya.

37. Namansu da jininsu ba sa zuwa wajen Allah, sai dai takawarku ce za ta isa gare Shi. Kamar haka Ya hore muku su don ku girmama Allah bisa shiryarwar da Ya yi muku (da addininsa). Kuma ka yi albishir ga masu kyautatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci rakuma da shanu waɗanda ya hore wa mutane su don su zama abin da za su riƙa yankawa a hadayarsu da layyarsu, ya sanya su alamomi ne na addininsa, ya kuma tabbatar da cewa a tare da su akwai abubuwan amfani masu yawa ga Musulmi, na duniya da na lahira. Haka kuma ya umarce su da ambaton sunan Allah idan sun zo soke su, musamman rakuma bayan sun tsaya da ƙafafunsu uku an ɗaure ɗayar domin kada su fizge su gudu. To idan sun faɗi bayan an soke an gyara su sun zama daidai a ci, sai ya umarce su da su ci wani kaso daga gare su, sannan su yi kyauta da wani kaso ga mabukacin da ya kame kansa ba ya roƙo, da ma wanda yake roƙo shi ma a ba shi.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) , ya ga wani mutum ya gurfanar da rakumarsa zai soke ta, sai ya ce masa: “Tashe ta tsaye a kan ƙafafuwanta, ka dabaibaye su, wannan ita ce sunnar Baban Kasimu (ﷺ).” [Bukhari #1713 da Muslim #1320].

Dangane da ni’imomin da Allah ya yi wa mutane a kan waɗannan dabbobi kuma ya bayyana cewa, ya hore musu su don su hau su ɗora musu kaya, kuma su yanka ko su soke domin neman kusanci ga Allah. Allah ya yi wa mutane wannan ne don su gode masa a kan ni’imominsa su yi masa biyayya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa masu layya ko hadaya cewa ba ruwansa da namansu ko jininsu; abin da kawai Allah yake la’akari da shi, yake kuma sakayya a kansa shi ne takawa, watau masu layya ko hadaya su yi don Allah kawai ba don fariya ko riya ba. Sannan Allah ya ƙara tabbatar da ni’imar da ya yi wa mutane na hore musu waɗannan dabbobi domin su yi wa Allah kabbara su kuma gode masa bisa ga dacen bin hanyar gaskiya da ya yi musu. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya yi albishir ga masu kyautata ibadarsu da mu’amalolinsu da mutane.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani mumini yana samun kariyar Allah ne gwargwadon imaninsa; wani ya samu da yawa wani kuma ya samu ‘yar kaɗan.

2. Haɗarin cin amanar Allah ko ta bayinsa, domin duk mai yin haka, to ya yi asarar samun soyayya ta Ubangiji. Wannan ya nuna Allah yana son duk wani mumini mai riƙon amana mai gode wa Allah.

3. Tabbatar da halaccin jihadi don kare wuraren bautar Allah.

4. Riƙo da Musulunci shi ne zai jawo samun nasarar Musulmi a kan abokan gabarsu.

Suratul Hajji (38-41)

*إِنَّ ٱللَّهَ يُدَٰفِعُ عَنِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ خَوَّانٍ كَفُورٍ ۝٣٨ أُذِنَ لِلَّذِينَ يُقَٰتَلُونَ بِأَنَّهُمۡ ظُلِمُواْۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ نَصۡرِهِمۡ لَقَدِيرٌ ۝٣٩ ٱلَّذِينَ أُخۡرِجُواْ مِن دِيَٰرِهِم بِغَيۡرِ حَقٍّ إِلَّآ أَن يَقُولُواْ رَبُّنَا ٱللَّهُۗ وَلَوۡلَا دَفۡعُ ٱللَّهِ ٱلنَّاسَ بَعۡضَهُم بِبَعۡضٖ لَّهُدِّمَتۡ صَوَٰمِعُ وَبِيَعٞ وَصَلَوَٰتٞ وَمَسَٰجِدُ يُذۡكَرُ فِيهَا ٱسۡمُ ٱللَّهِ كَثِيرٗاۗ وَلَيَنصُرَنَّ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِيٌّ عَزِيزٌ ۝٤٠ ٱلَّذِينَ إِن مَّكَّنَّٰهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَمَرُواْ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَنَهَوۡاْ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۗ وَلِلَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلۡأُمُورِ ۝٤١

38. Haƙiƙa Allah Yana bayar da kariya ga waɗanda suka yi imani. Lalle Allah ba Ya son duk mai ha'inci, butulu.

39. An yi izini (na yin yaƙi) ga waɗanda ake yaƙa don ko lalle an zalunce su. Lalle kuma Allah Mai iko ne bisa taimakon su.

40. (Su ne) waɗanda aka fitar da su daga gidajensu ba da wani laifi ba, sai don kawai sun ce: "Allah ne Ubangijinmu". Kuma ba don kariyar Allah ga wasu mutane ta hanyar wasu ba, to da lalle an rusa wuraren bauta (na Nasara da suka ƙaurace wa 'yan'uwansu), da coci-coci da wuraren bautar Yahudawa da masallatai (na Musulmi) waɗanda ake ambaton sunan Allah da yawa a cikinsu. Kuma tabbas Allah zai taimaki mai taimakon Sa. Lalle Allah Mai ƙarfi ne, Mabuwayi.

41. (Su ne) waɗanda, idan Muka kafa su a bayan ƙasa sai su tsai da salla su kuma ba da zakka kuma su yi umarni da aikin alheri su kuma yi hani daga mummunan aiki. Ƙarshen al'amura kuwa na Allah ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi ne yake kare muminai daga sharrin maƙiyansu saboda imaninsu, amma kuma ba ya son duk wani mai cin amanar Allah da ta bayinsa, mai butulce wa ni'imomin Allah ba ya gode masa a kansu.
Allah kuma ya sanar da muminai cewa ya yi musu izinin su tashi su yaƙi azzalumai don kare kansu daga waɗanda suka zalunce su, suka cutar da su., lokacin da Musulmi suke a Makka kafin su yi hijira zuwa Madina. Kafiran Kuraishawa sun takura wa Annabi (ﷺ) da sahabbansa, sun yi ta cutar da su da zagi da duka da duk wani salo na ƙunci wulaƙanci da cin mutunci. Amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai ba wa Musulmi izini su yi yaƙi ba a lokacin, ya umarce su ne da su ci gaba da haƙuri da afuwa da kawar da kai. Bayan sun yi hijira sun kafa Daularsu a Madina sun yi ƙarfi sai Allah ya umarce shi da su tashi su kare kansu su yaƙi waɗanda suke zaluntar su, ya kuma yi musu alƙawarin ba su nasara a kan maƙiyansu domin shi Allah mai iko ne a kan komai.
Sai kuma ya ambaci irin zaluncin da kafirai suka riƙa yi wa Musulmi, na fitar da su daga gidajensu ba tare da sun yi musu laifin komai ba, sai don zalunci da kuma cewa sun yi imani Allah ne Ubangijinsu abin bautar su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ba domin ya shar'anta wa annabawa da muminai su tashi su kare kansu da wuraren ibadarsu daga ta'addancin kafirai ba, to ba shakka da sun aiwatar da ta'addancinsu a kan wuraren bauta masu yawa, da sun rushe wuraren bauta na Nasara da suke ƙaurace wa mutane suna bautar Allah a cikinsu, da kuma coci-coci na Nasara da wuraren bautar Yahudawa da masallatan Musulmi waɗanda aka tanade su domin salla, kuma Musulmi suke ambaton Allah da yawa a cikinsu.
Sannan Allah ya ƙara tabbatar da cewa lalle ya yi alƙawarin sai ya taimaki duk mai taimakon addininsa, lalle kuma shi mai ƙarfi ne Mabuwayi, babu mai iya ja da shi ya yi nasara.

An karƀo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Yayin da aka fitar da Annabi (ﷺ) daga Makka sai Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Sun kori Annabinsu! *Inna lillahi wa inna ilaihi raji’un*, tabbas kuwa za su hallaka, sai Allah ya saukar da wannan ayar ta 39.” Ibnu Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Daga lokacin aka fahimci sai an yi yaƙi (watau tsakanin Musulmi da kafirai).” Ibnu Abbas ya ƙara da cewa: “Wannan ita ce farkon ayar da ta sauka game da yaƙi.” [Ahmad #1865 da Tirmizi #3171].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗannan muminai da ya yi musu alƙawarin ba su nasara su ne waɗanda, idan ya kafa su a bayan ƙasa ya ba su iko da galaba a kan abokan gabarsu, to lalle za su tsayar da salla kamar yadda ya kamata, kuma za su fitar da zakkar dukiyoyinsu, za kuma su yi umarni da kyakkyawan aiki wanda shari’a ta yi umarni da shi, za su kuma hana aikata abin da aka hana.
Sannan ya ƙara tabbatar da cewa ƙarshen al’amura duka gare shi za su koma, don haka shi ne mai bayar da lada shi ne kuma mai yin uƙuba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutanen Annabi Musa su ne Banu Isra’ila, ba kuma su ne suka ƙaryata shi ba; waɗanda suka ƙaryata shi su ne Fir’auna da mutanensa Kibɗawa.

2. Ba a ambaci mutanen Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a cikin mutanen da aka hallaka ba a sauran ayoyin Alƙur’ani sai a wannan ayar duk da cewa ba a saukar musu azaba irin wadda aka saukar wa sauran al’ummu da suka ƙaryata manzanninsu ba. An dai ambace su ne a nan saboda sun fi kamanni da kafiran Kuraishawa, domin su ma sun ƙaryata Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun yi sanadiyyar ƙaurace wa garinsa, kamar yadda kafiran Kuraishawa su ma suka yi wa Manzon Allah (ﷺ).

3. Jinkirta azaba ga mai laifi ba yana nufin ya kuɓuta ne ba. Ana jinkirta masa ne don ya ƙara wa kansa tsananin azaba da ƙarin kafirci da saɓon Allah da zai yi ta yi.

4. Duk wanda ba ya wa’azantuwa da abin da yake ji yana gani na ayoyin Allah, wannan shi ne mai makauniyar zuciya. Kuma makantar zuciya ita ce makanta mafi muni da haɗari ba makantar ido ba.

5. Amfanin tafiye-tafiye a bayan ƙasa shi ne mutum ya gane wa idonsa abin da zai zamo masa wa’azi ya ƙara masa tsoron Allah da halarto da girmansa a zuciyarsa.

Suratul Hajji (42-46)
وَإِن يُكَذِّبُوكَ فَقَدْ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ وَعَادٌ وَثَمُودُ ﴿٤٢﴾ وَقَوْمُ إِبْرَٰهِيمَ وَقَوْمُ لُوطٍ ﴿٤٣﴾ وَأَصْحَٰبُ مَدْيَنَ ۖ وَكُذِّبَ مُوسَىٰ ۖ فَأَمْلَيْتُ لِلْكَٰفِرِينَ
ثُمَّ أَخَذْتُهُمْ ۖ فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِ ﴿٤٤﴾ فَكَأَيِّن مِّن قَرْيَةٍ أَهْلَكْنَٰهَا وَهِىَ ظَالِمَةٌ فَهِىَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا وَبِئْرٍ مُّعَطَّلَةٍ وَقَصْرٍ مَّشِيدٍ ﴿٤٥﴾ أَفَلَمْ
يَسِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَتَكُونَ لَهُمْ قُلُوبٌ يَعْقِلُونَ بِهَآ أَوْ ءَاذَانٌ يَسْمَعُونَ بِهَا ۖ فَإِنَّهَا لَا تَعْمَى ٱلْأَبْصَٰرُ وَلَٰكِن تَعْمَى ٱلْقُلُوبُ ٱلَّتِى فِى ٱلصُّدُورِ ﴿٤٦﴾

42. Idan kuwa suka ƙaryata ka, to haƙiƙa mutanen Nuhu da Adawa da Samudawa sun ƙaryata (manzanni) kafin su.

43. Da mutanen Ibrahimu da mutanen Luɗu (su ma sun ƙaryata).

44. Da ma mutanen Madyana (su ma sun ƙaryata); an kuma ƙaryata Musa, sai Na jinkirta wa kafurai, sannan Na kama su (da azabata); to ƙaƙa (ƙarshen) kashedina (a gare su) ya kasance?

45. Sannan alƙarya nawa muka hallaka su alhalin suna azzalumai, sai ga su suna rugurguje a kan rufinsu sun zama kufai, da kuma rijiyoyin da aka watsar da amfani da su, da manya-manyan gine-gine da aka ɗaukaka su?

46. Yanzu ba za su yi tafiya a bayan ƙasa ba don su samu zukata da za su riƙa tunani da su, ko kuwa kunnuwa da za su riƙa ji da su? To lalle yadda lamarin yake ba idanduna ba ne suke makancewa sai dai zukatan da suke cikin ƙiraza su ne suke makancewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Annabi (ﷺ) game da ƙaryatawar da mutanensa suke yi masa, da cewa, idan har sun ci gaba da ƙaryata shi to ya yi haƙuri, ba shi ne farkon annabin da mutanensa suka ƙaryata ba; mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ƙaryata shi; Adawa sun ƙaryata Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su ma Samudawa sun ƙaryata Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Hakanan mutanen Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ƙaryata shi; mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ma sun ƙaryata shi, mutanen Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ƙaryata Annabi Shu'aibu, Fir'auna da mutanensa sun ƙaryata Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). To amma dukkansu Allah ya jinkirta azabtar da su, daga ƙarshe ya kama su mummunan kamu. Allah ya ja hankalin Annabi (ﷺ) da cewa ya duba ya ga yadda ƙarshen kashedin da ya yi musu ya zamanto a gare su, domin kuwa dukkansu ya hallaka su saboda kafircinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ba waɗancan al'ummu ne kawai ya hallaka ba, ya hallaka al'ummu masu yawa yayin da suka yi zalunci da kafirci da shirka da ƙaryata manzanni, ya yi rugurugu da alƙaryunsu suka wayi gari babu wasu mazauna a cikinsu; rijiyoyinsu aka yi watsi da su da manya-manyan gine-gine na alfarma waɗanda suka kasa kare su daga azabar Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga kafirai idan har suna tababa game da wannan batu, to me zai hana su yi tattaki su ziyarci waɗannan alƙaryu su ga yadda Allah ya hallaka mazauna cikinsu ya bar su kufai babu kowa a wurin, sai su yi tunani da hankulansu don su wa'azantu, su kuma buɗe kunnuwansu su saurari labaransu sauraro na fahimta da aiki, domin makanta ta haƙiƙa ba ita ce rasa idanu ba; haƙiƙanin makanta mai hallakarwa ita ce makantar zuci wadda take hana mutane karɓar gaskiya da aiki da ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gaggawa ɗabi'a ce ta ɗan'adam, amma gaggauto da azabar Allah wannan rashin hankali ne da wauta.

2. Rayuwar alƙiyama ba daidai take da rayuwar duniya ba har a tsawon kwanaki.

3. Mummunan ƙarshen azzalumai.

4. Babban aikin kowane manzo shi ne gargaɗi da albishir.

5. Bayanin sakamakon muminai da kafirai a ranar lahira.

وَيَسۡتَعۡجِلُونَكَ بِٱلۡعَذَابِ وَلَن يُخۡلِفَ ٱللَّهُ وَعۡدَهُۥۚ وَإِنَّ يَوۡمًا عِندَ رَبِّكَ كَأَلۡفِ سَنَةٖ مِّمَّا تَعُدُّونَ ٤٧ وَكَأَيِّن مِّن قَرۡيَةٍ أَمۡلَيۡتُ لَهَا وَهِيَ ظَالِمَةٞ ثُمَّ أَخَذۡتُهَا وَإِلَيَّ ٱلۡمَصِيرُ ٤٨ قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّمَآ أَنَا۠ لَكُمۡ نَذِيرٞ مُّبِينٞ ٤٩ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٥٠ وَٱلَّذِينَ سَعَوۡ فِيٓ ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ٥١

47. Kuma suna neman ka da gaggauto musu da azaba, Allah kuwa ba Ya saɓa alƙawarinsa. Lalle kuma yini ɗaya a wurin Ubangijinka kamar shekara dubu ne daga irin waɗanda kuke ƙirgawa.

48. Kuma alƙaryu nawa ne Na saurara musu, alhali kuwa suna kafirai, sannan (daga baya) Na kama su? Makoma kuma zuwa gare Ni ne.

49. Ka ce: “Ya ku mutane, ni dai kawai mai gargaɗi ne a gare ku mai bayyana (gargaɗi).”

50. To waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki na gari, suna da gafara da kuma arziki mai girma.

51. Waɗanda kuwa suka yi iya ƙoƙarinsu game da ɓata ayoyinmu suna ganin za su gagare Mu, to waɗannan su ne ma’abota (wutar) Jahima.

A waɗannan ayoyi bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) a kan ƙuntatawar da mushirikai suke yi masa, sai kuma ya bayyana wani izgili da kafirai suke yi masa na neman ya gaggauto musu da azaba wadda yake yi musu barazana da ita ta duniya da ma ta lahira. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa su daina garaje domin wannan alƙawari ne na Allah kuma ba zai taɓa saɓa alƙawarinsa ba, domin ya fara gaggauto musu da wata azaba ta kisa a yaƙin Badar lokacin da aka kashe wasu manyan shugabannin Kuraishawa a wannan yaƙin. Bugu da ƙari kuma akwai ranar alƙiyama tana nan tafe wadda a cikinta ne za su gamu da mummunan sakamakon da yake jiran su. Kuma yini ɗaya na azabar wannan ranar kamar tsawon shekara dubu yake a lissafin shekarunsu na duniya saboda tsananin azabar da ke cikinsa. Wannan ya nuna cewa su ne suke ganin tsawon lokacin da aka ɗauka ba a zo musu da azabar da ake yi musu kashedinta ba.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Talakawan Musulmi za su riga masu wadatarsu shiga Aljanna da rabin yini, watau shi ne shekara ɗari biyar.” [Ahmad #8521 da Tirmizi #1354 da Ibn Majah #4122].

Sai kuma ya bayyana musu cewa jinkirin da yake yi musu ba saɓa alƙawari ne ba, talala ce yake yi musu, zai kama su a nan gaba, domin akwai al’ummu masu yawa a gabaninsu da suka yi zalunci na kafirci da saɓon Allah da cutar da junansu amma Allah bai gaggauto musu da azaba ba, ya yi musu talala har sai da lokacin kama su ya zo sai ya yi musu mummunan kamu, ya hallaka su baki ɗaya. Makomarsu gaba ɗayansu kuma zuwa gare shi take, watau ranar alƙiyama a nan ne zai yi musu sakamako da azabar wuta ta har abada saboda kafircinsu.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya sanar da su cewa shi Manzo ne mai gargaɗi bayyananne a gare su, don haka gaggauto da azaba ba a hannunsa take ba tana hannun Allah ne; idan ya ga dama ya gaggauto ta, idan kuma ya ga dama ya yafe wa wanda ya tuba ya koma gare shi.
Sai kuma ya bayyana cewa waɗanda suka yi imani da Allah kuma suka yi kyawawan ayyuka, Allah ya tanadar musu gafara ga zunubansu da wani arzuki na karamci mai ɗorewa a gidan Aljanna. Amma waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah suna tsammanin ko za su gagari Allah su kuɓuce wa azabarsa, to waɗannan su ne ma’abota wutar Jahannama; za su shige ta su yi ta zama a cikinta har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da bambanci tsakanin manzo da annabi. Manzo shi ne wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika shi zuwa ga kafirai ‘yan jahiliyya. Annabi kuwa shi ne wanda Allah ya aika shi zuwa ga mutanen da ba ‘yan jahiliyya ba, amma kuma suna da buƙatar ilimi da jaddada musu addininsu.

2. Shi ma annabi ɗan aike ne kamar manzo, don haka wajibi ne a kansa ya isar da saƙon da aka aiko shi da shi.

3. Kariyar Allah ga littafinsa daga duk wani canji ko jirkitawa da tunkuɗe masa duk wani makircin Shaiɗan da mataimakansa.

4. Karkasuwar zukata zuwa kashi uku:
• **Ta ɗaya**, zuciya marar lafiya.
• **Ta biyu**, zuciya matacciya. Ita ce ƙeƙasasshiya.
• **Ta uku**, zuciya lafiyayya. Ita ce mai natsuwa.

5. Mutuwar zuciya da ƙeƙashewarta cututtuka ne masu haɗarin gaske ga zuciya.

6. Ingantaccen ilimi shi ne yake haifar da imani da natsuwa da ƙasƙantar da kai ga umarnin Allah.

Suratul Hajji (52-54)
وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٖ وَلَا نَبِيٍّ إِلَّآ إِذَا تَمَنَّىٰٓ أَلۡقَى ٱلشَّيۡطَٰنُ فِيٓ أُمۡنِيَّتِهِۦ فَيَنسَخُ ٱللَّهُ مَا يُلۡقِي ٱلشَّيۡطَٰنُ ثُمَّ يُحۡكِمُ ٱللَّهُ ءَايَٰتِهِۦۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٥٢ لِّيَجۡعَلَ مَا يُلۡقِي ٱلشَّيۡطَٰنُ فِتۡنَةٗ لِّلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ وَٱلۡقَاسِيَةِ قُلُوبُهُمۡۗ وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَفِي شِقَاقِۭ بَعِيدٖ ٥٣ وَلِيَعۡلَمَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَيُؤۡمِنُواْ بِهِۦ فَتُخۡبِتَ لَهُۥ قُلُوبُهُمۡۗ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهَادِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٥٤

52. Kuma babu wani manzo ko wani annabi da Muka aiko a gabaninka face idan ya yi karatu sai Shaiɗan ya jefa (ruɗu da wasiwasi) cikin karatunsa; sannan Allah Yakan ɓata abin da shi Shaiɗan yake jefawa, sannan Allah Ya tabbatar da ayoyinsa. Allah kuwa Masani ne Mai hikima.

53. (Yakan yi haka ne) don Ya sanya abin da Shaiɗan yake jefawa ya zama fitina ga waɗanda suke da cuta a cikin zukatansu, da kuma masu ƙeƙasassun zukata. Lalle kuma azzalumai tabbas suna cikin saɓani mai nisa.

54. Don kuma waɗanda aka bai wa ilimi su san cewa shi (Alƙur’ani) gaskiya ne daga Ubangijinka yake, sai su yi imani da shi sai zukatansu su nutsu da shi. Kuma lalle Allah tabbas Mai shiryar da waɗanda suka yi imani ne zuwa ga tafarki madaidaici.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Annabi (ﷺ) ne game da ƙaryata shi da mutanensa suka yi, da cewa babu wani manzo ko annabi da ya aiko gabaninsa face idan ya fito yana karanta wa mutane littafin Allah sai Shaiɗan ya yi ƙoƙarin jefa ruɗu da wasiwasi a cikin zukatan masu sauraron wannan karatun nasa domin ya hana su yin imani da abin da ake karanta musu, kamar yadda idan Annabi (ﷺ) yana karanta wa mushirikai Alƙur’ani Shaiɗan yakan jefa ruɗani a cikin zukatansu sai su riƙa kiran Annabi (ﷺ) da matsafi ko mawaƙi ko boka da sauran sunaye na banza, to amma sai Allah ya shafe wannan ruɗun da wasiwasin na Shaiɗan ya tabbatar da ayoyinsa na gaskiya, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) masanin komai ne mai hikima ne cikin ayyukansa gaba ɗaya.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kasa mutane gida uku dangane da ruɗun da Shaiɗan yake kawowa lokacin da Annabi yake karanta ayoyin Allah:
Kashi na farko, su ne munafukai masu cutar munafurci a zukatansu, sai wannan ya zame musu wata jarraba, sai munafurcinsu ya ƙaru, cutar zukatansu ta daɗa hauhawa.
Kashi na biyu, su ne mushirikai waɗanda zukatansu suka ƙeƙashe suka mutu murus, to sai su yi amfani da wannan ruɗin na Shaiɗan su riƙa hana mutane yin imani da gaskiya.
To duk waɗannan kaso biyun azzalumai ne masu nuna adawa ga Allah da Manzonsa (ﷺ) don haka sun yi nisa da gaskiya da shiriya.
Kashi na uku, su ne muminai waɗanda Allah ya ba su ilimi, to waɗannan za su san cewa lalle Alƙur'ani gaskiya ne kuma saukakke ne daga Allah Ubangijinsu, don haka sai su yi imani da shi, zukatansu kuma su nutsu da shi su miƙa wuya gare shi. Allah kuma ya tabbatar da cewa lalle zai shiryar da muminai zuwa ga hanyar gaskiya miƙaƙƙiya ɗoɗar wadda babu karkata a cikinta, sakamakon miƙa wuya da suka yi ga wahayin Ubangijinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda ya yi nisa a kafircinsa samuwar gamsassun hujjoji ba lalle su sanya shi ya yi imani ba.

2. A ranar lahira kafirai za su yi imani amma imaninsu ba zai yi musu amfani ba.

3. A ranar alƙiyama Allah zai yi hukunci na adalci tsakanin muminai da kafirai, kowa zai gane matsayinsa a wannan ranar.

Suratul Hajji (55-57)
وَلَا يَزَالُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي مِرۡيَةٖ مِّنۡهُ حَتَّىٰ تَأۡتِيَهُمُ ٱلسَّاعَةُ بَغۡتَةً أَوۡ يَأۡتِيَهُمۡ عَذَابُ يَوۡمٍ عَقِيمٍ ٥٥ ٱلۡمُلۡكُ يَوۡمَئِذٖ لِّلَّهِ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡۚ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ٥٦ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٞ مُّهِينٞ ٥٧

55. Waɗanda kuwa suka kafirce ba za su daina kokwanton sa ba (watau Alƙur'ani) har sai alƙiyama ta zo musu ba zato ba tsammani, ko kuma azabar rana bakarara ta zo musu.

56. Mulki a wannan ranar na Allah ne, zai yi hukunci a tsakaninsu. To waɗanda suka yi imani suka kuma yi kyawawan ayyuka, suna cikin gidajen Aljanna na ni'ima.

57. Waɗanda kuwa suka kafirta suka kuma ƙaryata ayoyinmu, to waɗannan suna da azaba mai wulaƙantawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kafirai ba za su daina halinsu na yin shakka game da Alƙur'ani ba, za su doge a kan haka har sai ranar alƙiyama ta zo musu ba zato ba tsammani, ko kuma azabar wannan ranar ta zo musu. A wannan ranar kafirai ba za su gamu da wata rahama ko wani alheri ba; za su yi ta nadamar da ba za ta yi musu amfani ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa mulki gaba ɗaya a wannan ranar a hannunsa yake, nasa ne shi kaɗai babu mai ja da shi. Shi ne zai yi hukunci tsakanin muminai da kafirai, kowanne ya yanke masa hukuncin da ya cancance shi. Waɗanda suka yi imani kuma suka yi ayyuka na gari, to waɗannan suna da babban sakamako na gidajen Aljannar ni'ima wadda ba ta yankewa. Waɗanda kuwa suka kafirta suka kuma ƙaryata ayoyin da Allah ya saukar wa Manzonsa, to waɗannan suna da azaba mai wulaƙantarwa ta wutar Jahannama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matsayin hijira a Musulunci da falalarta.

2. Halaccin wanda aka cuta ya rama gwargwadon yadda aka cuce shi. Amma ya yi haƙuri shi ya fi.

3. Idan Allah zai taimaki wanda aka cuce shi saboda ya rama cutar da aka yi masa, to lalle wanda ya yi haƙuri bai rama ba sai ya fi cancantar taimakon Allah da nasararsa.

4. Duk wani abin bauta ba Allah ba ƙarya ne, Allah ne kawai abin bauta na gaskiya wanda yake da tabbas.

5. Tabbatar wa da Allah siffofin ɗaukaka da girma.

Suratul Hajji (58-62)
وَٱلَّذِينَ هَاجَرُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ ثُمَّ قُتِلُوٓاْ أَوۡ مَاتُواْ لَيَرۡزُقَنَّهُمُ ٱللَّهُ رِزۡقًا حَسَنٗاۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ خَيۡرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ٥٨ لَيُدۡخِلَنَّهُم مُّدۡخَلٗا يَرۡضَوۡنَهُۥۗ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَعَلِيمٌ حَلِيمٞ ٥٩ ۞ذَٰلِكَۖ وَمَنۡ عَاقَبَ بِمِثۡلِ مَا عُوقِبَ بِهِۦ ثُمَّ بُغِيَ عَلَيۡهِ لَيَنصُرَنَّهُ ٱللَّهُۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَعَفُوٌّ غَفُورٞ ٦٠ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ يُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِ وَأَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعُۢ بَصِيرٞ ٦١ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ هُوَ ٱلۡبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡكَبِيرُ ٦٢

58. Waɗanda kuwa suka yi hijira saboda Allah sannan aka kashe su ko kuma suka mutu, to lalle Allah tabbas zai arzuta su da kyakkyawan arziki. Kuma lalle Allah tabbas Shi ne Fiyayyen masu arzutawa.

59. Lalle tabbas Zai shigar da su wata mashiga da za su yarda da ita. Kuma lalle Allah tabbas Masani ne, Mai hakuri.

60. Wannan (abu da aka ambata haka yake), duk wanda ya yi uƙuba da irin abin da aka yi masa uƙuba da shi, sannan aka daɗa yi masa ta'addanci, to lalle Allah tabbas zai taimake shi. Lalle Allah tabbas Mai afuwa ne, Mai gafara.

61. Wannan (taimakon kuwa zai kasance ne) saboda lalle Allah Shi Yake shigar da dare cikin rana, Yake kuma shigar da rana cikin dare, kuma lalle Allah Mai ji ne, Mai gani.

62. Wannan kuwa saboda lalle Allah Shi ne (abin bauta) na gaskiya, kuma lalle abin da suke bauta wa wanda ba Shi ba shi na ƙarya ne, kuma lalle Allah Shi ne Maɗaukaki, Mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi babban albishir ga waɗanda suka yi hijira don Allah suka bar garuruwansu da gidajensu domin neman yardar Allah da yaɗa addininsa, suka kuma fita jihadi aka kashe su a can, to waɗannan Allah ya yi musu alƙawarin tabbas zai arzuta su a gidan Aljanna da kyakkyawan arziki wanda ba zai yanke ba har abada, domin Allah shi ne fiyayyen masu arzutawa. Zai shigar da su wani wurin da za su yarda da shi, watau gidan Aljanna. Lalle Allah yana sane da ayyukansu da niyyoyinsu, kuma shi mai haƙuri ne, shi ya sanya ba ya gaggauto da uƙuba ga bayinsa da suka yi laifi, yana jinkirta musu ne domin su tuba ya yafe musu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk wanda aka cuce shi ko aka zalunce shi, to ya halatta a gare shi ya rama zaluncin da aka yi masa daidai da abin da aka yi masa; yin haka ba laifi ba ne.

Idan kuma bayan ya rama gwargwadon abin da aka yi masa, sai kuma aka sake yi masa wani ta'addancin don ramuwar da ya yi, to lalle tabbas Allah zai taimaka masa a kan wanda ya yi masa ta'addanci. Kuma Allah ya tabbatar da cewa shi mai afuwa ne ga muminai masu laifi, mai gafara ne gare su.
Sai kuma ya tabbatar da cikakkiyar Kudurarsa ta aikata abin da ya ga dama ga halittarsa, domin shi ne mai ikon shigar da lokutan dare a cikin na rana, ya kuma shigar da lokutan rana a cikin na dare ta hanyar ƙara tsawon ɗaya ya rage na ɗayan. Kuma shi ne wanda yake jin duk maganganun bayinsa yake kuma sane da ayyukansu, babu abin da yake ɓuya gare shi, kuma zai yi musu sakayya a kai.
Sai kuma ya tabbatar da cewa shi ne Allah wanda yake zartar da waɗannan ayyuka, wanda kuma ya siffantu da siffofin kamala. Don haka shi ne abin bauta na gaskiya, duk wani abu da wasu suke bauta wa ba Allah ba ƙarya ne wanda ba shi da wani tushe ko tabbas. Allah shi kaɗai ne wanda yake da ɗaukaka ta zati da siffa da iko, kuma shi ne mai girma wanda kowa a ƙasa da shi yake.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kira da jan hankali a kan duba da tunani game da halittun Allah masu nuna cikakkiyar Kudurarsa da tabbatar da Kaɗaitakarsa wajen bauta.

2. Allah shi kaɗai ne mai cikakkiyar wadata ta kowace fuska, domin shi ne ba ya buƙatar wani mahaluƙi ya taimaka masa da komai ko ya tallafa masa a cikin wani aikinsa. Shi ne wanda ba ya buƙatar mata ko ɗa; ba ya ci ba ya sha. Yana daga cikin wadatarsa da a ce halittun sama da na ƙasa da na farko da na ƙarshe za su haɗu kowa ya roƙe shi wata buƙata shi kuma ya biya musu duk buƙatunsu, da wannan ba zai rage masa komai daga cikin mulkinsa ba.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne Sha-yabo a Zatinsa da sunayensa domin zamantowarsu mafiya kyau; da siffofinsa domin kasancewarsu siffofi ne na kamala; da shari'arsa domin kasancewarsa ba ya umarni sai da abin da yake cike da maslaha da amfani ga bayinsa, ba ya hana wani abu sai wanda ya tabbata cewa mai cutarwa ne gare su. Don haka ya cancanci yabo ta kowace fuska.

4. Babu mai tausayi da rahama kamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) domin shi ne yake saukar da ni'imominsa ga ɗan'adam tutur ba dare ba rana, amma da dama daga cikinsu suna kafirce masa suna yi masa butulci, shi kuwa bai fasa hore musu waɗannan ni'imomi ba.

Suratul Hajji (63-66)
أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَتُصۡبِحُ ٱلۡأَرۡضُ مُخۡضَرَّةًۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَطِيفٌ خَبِيرٞ ٦٣ لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَهُوَ ٱلۡغَنِيُّ ٱلۡحَمِيدُ ٦٤ أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَٱلۡفُلۡكَ تَجۡرِي فِي ٱلۡبَحۡرِ بِأَمۡرِهِۦۚ وَيُمۡسِكُ ٱلسَّمَآءَ أَن تَقَعَ عَلَى ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا بِإِذۡنِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِٱلنَّاسِ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ ٦٥ وَهُوَ ٱلَّذِيٓ أَحۡيَاكُمۡ ثُمَّ يُمِيتُكُمۡ ثُمَّ يُحۡيِيكُمۡۖ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَكَفُورٞ ٦٦

63. Shin ba ka ga cewa Allah ne Ya saukar da ruwa daga sama ba, sai ƙasa ta zama koriya shar? Lalle Allah Mai tausasawa ne, Masani.

64. Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne. Kuma lalle Allah tabbas Shi ne Mawadaci, Sha-Yabo.

65. Shin ba ka ga cewa Allah Ya hore muku abin da yake cikin ƙasa, da kuma jiragen ruwa da suke gudu a cikin kogi da umarninsa, kuma Yake riƙe sama don kada ta faɗo a kan ƙasa, sai da izininsa? Lalle Allah Mai tausayi ne, Mai rahama ga mutane.

66. Shi ne kuma Wanda Ya raya ku sannan zai kashe ku sannan Ya (sake) raya ku. Lalle mutum tabbas mai yawan butulci ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana wa Manzonsa isar mulkinsa da cikakkiyar Kudurarsa ta aikata abin da ya ga dama, da cewa shi ne ya saukar da ruwan sama sai ƙasa ta wayi gari ta zama koriya shar saboda tsirran da suka fito daga cikinta. Allah kuma ya yi haka ne saboda tausayawarsa ga bayinsa ya samar musu abincin da za su ci su rayu, domin ya fi kowa sanin abin da zai zama maslaha da amfani a gare su, kuma babu abin da yake ɓuya a gare shi.
Sannan ya tabbatar musu da cewa duk abin da yake cikin sammai da wanda yake cikin ƙasa mallakarsa ne, kuma shi lalle Mawadaci ne ba shi da buƙata a wurin wani mahaluƙi kowane ne. Abin gode wa ne wanda kowa yake yi masa kirari da Sha-yabo.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzon (ﷺ) wasu dalilai na cikar ikonsa da kamalar Kudurarsa, da kuma ni'imominsa ga mutane, da cewa, shi ne ya hore musu duk abin da yake bayan ƙasa na dabbobi da sauran daskararrun abubuwa, kamar duwatsu da bishiyoyi da sauransu domin amfaninsu da biyan buƙatunsu na rayuwa. Hakanan kuma ya hore musu jiragen ruwa waɗanda suke kai-komo a cikin koguna daga gari zuwa gari ɗauke da mutane da kayayyakinsu. Shi ne kuma yake riƙe da sama domin kada ta faɗo a kan ƙasa sai da izininsa. Ba don rahamarsa da cikakkiyar Kudurarsa ba da sai ta faɗo a kan mutane duk ta hallaka su, to amma Allah shi mai tausayin mutane ne mai rahama gare su, wannan ya sa ya hore musu duk waɗannan abubuwa da aka ambata da ma wasu daban.
Sannan Allah ya ci gaba da lissafa ni'imominsa da dalilan ikonsa, da cewa shi ne ya halicci mutane daga babu ya hura musu rai; sannan bayan cikar ajalinsu shi ne zai karɓi rayukansu, sannan bayan mutuwarsu zai sake raya su domin ya yi musu hisabi a kan ayyukansu ya saka wa kowa da irin abin da ya cancanta, to amma duk da waɗannan ni'imomin na Ubangiji sai ga ɗan'adam yana jayayya wajen bautar sa, ko ya yi jayayya a kan cewa zai iya tashin matattu bayan mutuwarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cewa kowace al'umma Allah ya tsara mata hanyar shari'arta da rayuwarta mai ɗauke da hikima da adalci. Shi ma Manzon Allah ya zo da shari'arsa da hanyar rayuwa da Allah ya tsara masa, don haka rashin tunani ne wasu jahilai su fito suna jayayya a kan wannan shari'ar bayan hujjoji sun tabbata a kan cewa daga Allah take. Wajibi ne a kan duk wani Musulmi ya miƙa wuya ya sallama wa hukunce-hukuncen Allah ba tare da jayayya ba matuƙar ya yarda da manzancin Annabi (ﷺ).

2. Jayayyar masu jayayya da musun masu musu game da shari'ar Allah ba abu ne da zai sa mai kira zuwa ga Allah ya daina kiran da yake yi ba. Wajibi ne ya ci gaba da da'awarsa cikin hikima da wa'azi mai kyau.

3. Duk abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi na shari'a yana kan hanya madaidaiciya, ya kuma dace da lafiyayyen hankali da halittar ɗan'adam ta asali, watau fiɗira. Don haka duk wanda yake riƙe da shi to ya sami yaƙini a zuciyarsa cewa yana kan tafarki miƙaƙƙe.

Suratul Hajji (67-69)
لِّكُلِّ أُمَّةٍ جَعَلْنَا مَنسَكًا هُمْ نَاسِكُوهُ ۖ فَلَا يُنَازِعُنَّكَ فِي ٱلْأَمْرِ ۚ وَٱدْعُ إِلَىٰ رَبِّكَ ۖ إِنَّكَ لَعَلَىٰ هُدًى مُّسْتَقِيمٍ ﴿٦٧﴾ وَإِن جَٰدَلُوكَ فَقُلِ ٱللَّهُ أَعْلَمُ بِمَا تَعْمَلُونَ ﴿٦٨﴾ ٱللَّهُ يَحْكُمُ بَيْنَكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا كُنتُمْ فِيهِ تَخْتَلِفُونَ ﴿٦٩﴾

67. Kowacce al’umma Mun sanya mata hanyar (shari’a) da za su yi aiki da ita; to lalle kada su yi jayayya da kai game da lamarin (addini). Kuma ka yi kira zuwa ga (addinin) Ubangijinka; lalle kai tabbas kana bisa shiriya madaidaiciya.

68. Idan kuwa suka yi maka jayayya, sai ka ce: “Allah ne Ya fi sanin abin da kuke aikatawa.”

69. Allah zai yi hukunci a tsakaninku ranar alƙiyama game da abin da kuka kasance kuna sassaɓawa a kansa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kowace al’umma ya tanadar musu tasu shari’ar da za su yi aiki da ita, don haka shi ma Manzo (ﷺ) Allah ya ba shi tasa shari’ar da yake aiki da ita. Saboda haka bai dace mushirikai da mabiya sauran addinai su yi jayayya da shi game da tasa shari’ar ba, domin shi ne a kan gaskiya, su kam suna rayuwa ne a kan ɓata. Sai ya umarci Annabi (ﷺ) ya ci gaba da yi musu wa’azi, ya kira su zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, domin shi ne a kan tafarki madaidaici wanda ba shi da wata karkata sam-sam.
Sai kuma ya bayyana masa cewa, idan waɗannan kafirai sun dage a kan ci gaba da jayayya da shi bayan hujja ta bayyana gare su a fili, to ya mayar da al’amarinsa ga Allah ya fito fili ya faɗa musu cewa, Allah ne ya fi kowa sanin abin da suke aikatawa, don haka su jira za su ga sakamakon abin da suke aikatawa. Kuma su kwana da sanin cewa a ranar alƙiyama Allah zai yi hukunci na adalci tsakanin bayinsa muminai da kafirai game da abubuwan da suka yi saɓani a kansu na batutuwan addini da na rayuwa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da aƙidar imani da ƙaddara, watau yarda da cewa Allah ya riga ya san da duk wani abu da zai auku ya kuma rubuta shi tun fil azal a cikin Lauhul Mahfuzu.

2. Munin bin abin da aka samu iyaye da kakanni suna kai ido rufe ba tare da wata hujja daga Allah ko Manzonsa ba.

3. Yi wa Allah shirka babban zalunci ne.

4. Bayanin tsananin ƙiyayyar da mushirikai suke nuna wa muminai yayin da suke kiran su zuwa ga kaɗaita Allah da bauta.

5. Kafirai ba su da wata hanya ta kare kafircinsu da ɓatansu sai ta hanyar cutar da masu da’awa da wulaƙanta su.

Suratul Hajji (70-72)
أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا فِى ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۗ إِنَّ ذَٰلِكَ فِى كِتَٰبٍ ۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٌ ﴿٧٠﴾ وَيَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ سُلْطَٰنًا وَمَا لَيْسَ لَهُم بِهِۦ عِلْمٌ ۗ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِن نَّصِيرٍ ﴿٧١﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ تَعْرِفُ فِى وُجُوهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ٱلْمُنكَرَ ۖ يَكَادُونَ يَسْطُونَ بِٱلَّذِينَ يَتْلُونَ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِنَا ۗ قُلْ أَفَأُنَبِّئُكُم بِشَرٍّ مِّن ذَٰلِكُمُ ۚ ٱلنَّارُ وَعَدَهَا ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۖ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٧٢﴾

70. Shin ba ka sani ba cewa lalle Allah Yana sane da abin da yake cikin sama da wanda yake ƙasa? Lalle wannan yana cikin littafi (wato Lauhul-Mahafuzu). Lalle wannan mai sauƙi ne a wurin Allah.

71. Suna kuma bauta wa wanda ba Allah ba, abin da bai saukar da wani dalili ba game da shi, da kuma abin da ba su da ilimi game da shi. Azzalumai kuwa ba su da wani mataimaki.

72. Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu bayyanannu, to za ka ga alamar musantawa a fuskokin waɗanda suka kafirta, suna kamar za su auka wa waɗanda suke karanta musu ayoyinmu. To ka ce: “Shin ba na ba ku labarin abin da ya fi wannan muni ba? Wuta ce da Allah Ya yi alƙawari ga waɗanda suka kafirta; makoma kuwa ta munana.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Annabi (ﷺ) cewa yana sane da duk abin da yake cikin sama da duk abin da yake a bayan ƙasa; domin kuwa komai yana nan a rubuce a cikin Lauhul Mahfuzu, don haka sanin komai abu ne mai matuƙar sauƙi a wurinsa.
Sai kuma ya bayyana cewa duk da kasancewar Allah ne mai wannan faffaɗan ilimi, mushirikai sun bijire a kan bautar sa shi kaɗai, sun ci gaba da bauta wa wasu gumaka waɗanda Allah bai taɓa saukar da wata hujja a cikin wani littafinsa kan cewa a bauta musu ba, su kansu masu bautar ba su da wani dalili da suka dogara da shi na bauta wa wani tare da Allah, wanda ya wuce cewa, suna bin abin da suka sami iyayensu ne a kai ido rufe. Wannan shirka da suke yi wa Allah tabbas babu zaluncin da ya kai shi. Don haka idan azabar Allah ta sauko musu ba su da wani wanda zai iya taimaka musu ya kare su daga gare ta.
Sai kuma ya bayyana irin taurin kansu da bijirewarsu yayin da suka ji ana karanta musu ayoyin Allah bayyanannu masu kira zuwa ga kaɗaita Allah da bauta, lokacin ne za a ga alamar fushi da musuntawa da bijirewa ta bayyana a fuskokinsu, har ma saboda tsananin fushi sai su yi kamar za su auka wa waɗanda suke karanta musu ayoyin. To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, idan suna ganin munin abin da yake karanta musu, hakan kuma yana ɗaga musu hankali, to ya yi musu albishir da wani abu da ya fi wannan muni a gare su, watau wutar Jahannama da Allah ya yi musu tanadinta kuma lalle zai shigar da su cikinta. Wannan makoma ta wutar Jahannama kuwa ta yi matuƙar muni.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mahimmancin ba da misali don ƙara fito da wasu abubuwa fili, wanda kuma yin haka hanya ce ta tarbiyya mai amfani.

2. Allah ne kaɗai mai cikakkiyar Kudura da zai iya yin halitta, don haka shi kaɗai ne ya cancanci a bauta masa.

3. Rashin girmama Allah shi ne yake jawo har a haɗa shi da wasu wajen bauta.

4. Manzanci zaɓi ne daga Allah ba yin mala’ika ne ko mutum ba.

5. Manzannin Allah cikin mala’iku da mutane zaɓaɓɓu ne masu daraja ta musamman.

Suratul Hajji (73-76)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ضُرِبَ مَثَلٞ فَٱسۡتَمِعُواْ لَهُۥٓۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَن يَخۡلُقُواْ ذُبَابٗا وَلَوِ ٱجۡتَمَعُواْ لَهُۥۖ وَإِن يَسۡلُبۡهُمُ ٱلذُّبَابُ شَيۡـٔٗا لَّا يَسۡتَنقِذُوهُ مِنۡهُۚ ضَعُفَ ٱلطَّالِبُ وَٱلۡمَطۡلُوبُ ٧٣ مَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ قَدۡرِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِيٌّ عَزِيزٌ ٧٤ ٱللَّهُ يَصۡطَفِي مِنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلٗا وَمِنَ ٱلنَّاسِۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعُۢ بَصِيرٞ ٧٥ يَعۡلَمُ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ ٧٦

73. Ya ku mutane, an ba da misali, to sai ku saurare shi. Lalle waɗanda kuke bauta wa ba Allah ba, ba za su taɓa iya halittar ƙuda ba, ko da sun taru domin (halitta) shi; idan kuma da ƙudan zai cire musu (su gumakan) wani abu, to ba za su iya ƙwato shi ba daga wurinsa. Wanda yake nema da wanda ake nema (duka) sun yi rauni!

74. Ba su girmama Allah ba kamar yadda ya kamata su girmama Shi. Lalle Allah tabbas Kaƙƙarfa ne, Mabuwayi.

75. Allah Yana zaɓar manzanni daga mala'iku kuma daga mutane. Lalle Allah Mai ji ne, Mai gani.

76. Yana sane da abin da yake gabansu da abin da yake bayansu. Zuwa ga Allah ne kawai ake komar da al'amura.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ƙaƙƙarfar hujja ta rashin cancantar bautar da kafirai suke yi wa abin bautarsu da cewa, ba sa iya tsinana wa kansu wani abu, ko su kare kansu daga wata cuta balle har su kare wani.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo wa mushirikai wani sassauƙan misali wanda za su saurara ko ya zame musu abin izina, da cewa, abin da suke bauta wa wanda ba Allah ba, ba zai iya halittar ko da ƙuda ba saboda kasawarsa, ko da kuwa za su yi taron dangi don wannan aikin. Hasali ma, da abin a ce ƙuda zai sauka a kan gumakan ya ɗauke musu wani abu, kamar turaren da ake saka musu a jiki, to fa ba za su iya ƙwato shi ba. To idan har ba za su iya halittar ƙanƙanin abu kamar ƙuda ba, ba kuma za su iya ƙwato wani abu daga wajensa ba, to ta yaya za a yi tsammanin za su iya halittar abin da ya fi ƙuda girma? To amma duk da haka saboda ɓata suna bauta musu ba Allah ba. Sai Allah ya tabbatar da cewa shi mai neman, watau gunkinsu, da wanda ake nema, watau ƙudan, duk sun tabbata masu rauni ne; wanda ya fi su rauni kuma shi ne wanda zai rungumi abu mai rauni a matsayin abin bauta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kafirai ba su ba wa Allah girman da ya kamata su ba shi ba, domin sun bauta wa wasu tare da shi. Lalle Allah ƙaƙƙarfa ne, mabuwayi. Yana daga cikin ƙarfinsa da buwayarsa ikon halittar sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu, kuma babu mai iya rinjayar sa a komai, saɓanin tarkacen da mushirikai suke bauta wa, waɗanda suke ƙaskantattu ne ba sa ma iya yi wa kansu komai balle su yi wa wani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimarsa da cewa shi ne yake zaɓar manzanni daga cikin mala'iku da kuma mutane. Yakan aiko wasu mala'ikunsa zuwa ga annabawa, kamar yadda ya riƙa aiko Mala'ika Jibrilu zuwa ga manzanni daga cikin mutane; su kuma manzanni ya aika su zuwa ga mutane. Ya tabbatar da cewa yana jin duk abin da mushirkai suke faɗa dangane da manzanninsa mutane. Ya kuma san halin da dukkanin manzanni na mala'iku da na mutane suke ciki gabanin halittarsu da bayan mutuwarsu. Ya tabbatar musu da cewa makomar dukkan al'amura tana gare shi shi kaɗai ranar alƙiyama, zai kuma yi wa kowa sakayya a kan abin da ya aikata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar salla da aikin alheri. Babu wata hanya ta rabauta sai cikin bautar Allah da ayyukan alheri domin amfanar da bayin Allah.

2. Babu tsanani a cikin koyarwar Musulunci.

3. Duk wani ƙunci da tsanani an ɗauke wa wannan al'umma shi.

4. Wannan al'umma al'umma ce zaɓaɓɓiya a wurin Allah, domin ya zaɓa mata mafi cikar addini, watau Musulunci, ya zaɓa mata mafi girman littattafai, watau Alƙur'ani, ya kuma zaɓa mata mafi darajar manzanni, watau Annabi Muhammadu (ﷺ).

5. Falalar wannan al'umma a kan sauran al'ummu, don haka ta zamanto mai shaida a kan sauran al'ummu.

Suratul Hajji (77-78)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱرۡكَعُواْ وَٱسۡجُدُواْ وَٱعۡبُدُواْ رَبَّكُمۡ وَٱفۡعَلُواْ ٱلۡخَيۡرَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٧٧ وَجَٰهِدُواْ فِي ٱللَّهِ حَقَّ جِهَادِهِۦۚ هُوَ ٱجۡتَبَىٰكُمۡ وَمَا جَعَلَ عَلَيۡكُمۡ فِي ٱلدِّينِ مِنۡ حَرَجٖۚ مِّلَّةَ أَبِيكُمۡ إِبۡرَٰهِيمَۚ هُوَ سَمَّىٰكُمُ ٱلۡمُسۡلِمِينَ مِن قَبۡلُ وَفِي هَٰذَا لِيَكُونَ ٱلرَّسُولُ شَهِيدًا عَلَيۡكُمۡ وَتَكُونُواْ شُهَدَآءَ عَلَى ٱلنَّاسِۚ فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱعۡتَصِمُواْ بِٱللَّهِ هُوَ مَوۡلَىٰكُمۡۖ فَنِعۡمَ ٱلۡمَوۡلَىٰ وَنِعۡمَ ٱلنَّصِيرُ ٧٨

77. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi ruku'i kuma ku yi sujjada, ku kuma bauta wa Ubangijinku, kuma ku aikata alheri don ku rabauta.

78. Kuma ku yi jihadi wajen (ɗaukaka addinin) Allah iyakar iyawarku. Shi ne Ya zaɓe ku, bai kuma sanya muku wani ƙunci ba cikin addini. Addinin Babanku ne Ibrahimu. (Allah) Shi ne Ya kira ku Musulmi tuntuni, da kuma cikin wannan (Alƙur'ani) don Manzo ya zama shaida a gare ku, ku kuma ku zama shaida ga (sauran) mutane. To sai ku tsai da salla kuma ku ba da zakka, ku kuma yi riƙo da (addinin) Allah, Shi ne Majiɓincin al'amarinku; to madalla da Majiɓinci, kuma madalla da Mataimaki.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga muminai waɗanda suka yi imani da Allah suka kuma yi ayyuka na ƙwarai, ya umarce su da yin ruku'u da sujjada a cikin sallolinsu ga Allah shi kaɗai. Sannan ya umarce su da aikata alheri ga mutane, kamar sadaka da taimako da sada zumunci domin su sami babban rabo kuma su kuɓuta daga duk wani abin ƙi.
Allah kuma ya umarce su da yin jihadi domin shi, ya tabbatar musu cewa shi ne ya zaɓa musu addini mai sauƙi wanda babu ƙunci ko tsanani a cikinsa, kuma shi ne addinin babansu Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya tura shi Yaman tare da Mu'azu ɗan Jabal (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce musu: "Ku sauƙaƙa kada ku tsananta, ku yi wa mutane albishir kada ku kore su; ku haɗa kawunanku kada ku saɓa." [Bukhari #3038 da Muslim #1733].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle wannan addini ne mai sauƙi babu wanda zai ɗora wa kansa abin da ya fi ƙarfinsa na addini sai ya rinjaye shi…" [Bukhari #39].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Manzon Allah (ﷺ) wane addini ne Allah ya fi so, sai ya ce: "Addinin Annabi Ibrahimu mai sauƙi." [Ahmad #2107].

Sannan kuma Allah ya tabbatar musu da cewa shi ne ya sa musu suna 'Musulmi' a cikin littattafan da suka gabata da kuma cikin Alƙur'ani, domin Manzo ya zama mai shaida a gare ku cewa ya isar muku da saƙon Allah, ku kuma ku zama masu shaida a kan sauran al'ummun da suka gabace ku cewa manzanninsu sun isar musu da saƙo. [Duba Tafsirin aya ta 143 cikin *Suratul Baƙara*].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su tsayar da salla yadda ya kamata, su kuma ba da zakkar dukiyoyinsu, su kuma yi riƙo da hanyar Allah, su dogara da shi cikin dukkan lamuransu, domin Allah shi ne majiɓincin al'amuransu; madalla da majiɓinci kuma madalla da mai taimakon wanda ya nemi taimakonsa daga cikin muminai. Don haka kowa ya nemi taimakonsa zai taimaka muku.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman martabar muminai da ambaton kyawawan ayyukansu wanda ake son kowa ya yi koyi da su domin ya zamanto ɗaya daga cikinsu.

2. Falalar natsuwar zuciya yayin salla, watau mai salla ya riƙa halarto wa zuciyarsa cewa yana tsaye ne a gaban Allah, ya ture duk wani waswasi da kowane irin tunani ban da sallar da yake ciki.

3. Idan bawa ya iya kame harshensa in ba a wajen faɗar alheri ba, to wannan shi ne wanda ya iya mallakar al'amarinsa, don haka siffar muminai ta zamanto ita ce kame harshensu daga faɗin maganganun banza ko na saɓon Allah.

4. Yana daga cikin kiyaye farji nisantar duk wani abu da zai jawo faɗawa cikin zina, kamar kallo na sha'awa da shafa da makamantansu.

5. Aya ta 5 zuwa ta 7 ta nuna haramcin auren mutu'a, domin matar mutu'a ba matar aure ce ba ta gaskiya, shi ya sa ba ta cin gado ba ta takaba ga wanda ya aure ta ta wannan hanyar, sannan ita kuma ba baiwa ce ba.

Hakanan ayar ta ƙunshi haramcin auren kashe-wuta, watau namiji ya auri matar da aka yi mata saki uku da niyyar ya halatta mata komawa ga mijinta na farko da wannan aure.
Imamus Shafi'i da wasu malamai kuma sun kafa hujja da wannan ayar a kan haramcin yin amfani da hannu don gusar da sha'awa, domin yin haka ba ya daga cikin hanyoyi biyu da Allah ya ambata, watau matar aure ko baiwar mutum; don haka ya shiga ƙarƙashin ƙetare iyaka da ya ambata a aya ta 7.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara shiga Aljanna ta hanyar aikata wasu ayyuka na gari da ya shar'anta, don haka abu ne mai kyau ga bawa ya san su ya kuma yi aiki da su



23-Suratul Mu’uminun

Mabuɗin Sura:

8. Sunanta:
Ana kiran ta da suna ‘*Suratul Mu’uminun*’ saboda an buɗe ta da bayanin siffofin muminai da sakamakonsu.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Sa’ib ya ce: “Annabi (ﷺ) ya yi mana sallar Asuba a Makka sai ya fara karatu daga farkon ‘*Suratul Mu’uminun*’ har sai da ambaton Musa da Haruna ya zo ko kuma ambaton Isa sai tari ya kama Annabi (ﷺ) sai ya yi ruku’u.” [Muslim #455 da Abu Dawud #649 da Nasa’i #1007 da Ibn Majah #820].

9. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa Sura ce *Makkiyya*.

10. Adadin Ayoyinta:
Yawancin malamai suna ganin ayoyinta ɗari ne da goma sha tara (119). Amma malaman Kufa suna ganin adadinsu ɗari ne da goma sha takwas (118).

11. Jerin Saukarta:
Ita ce sura ta saba’in da shida (76) a jerin saukar surori; ta sauka bayan *Suratuɗ Ɗuri* gabanin *Suratul Mulki*.

12. Babban Jigonta:
Magana a kan haƙiƙanin imani da amfaninsa da magana a kan mummunan sakamakon waɗanda suka ƙi yin imani suka ƙaryata manzannin Allah.

13. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Ta buɗe da yi wa muminai albishir da samun babban rabo saboda kyawawan siffofin da suka siffantu da su.
• Magana a kan asalin jinsin ɗan’adam da matakan halittar ɗan’adam a cikin mahaifiyarsa.
• Jan hankali game da ɗaukar izina daga halittar sammai da ruwa wanda shi ne jigon rayuwar komai a duniya; da jan hankali game da halittar dabbobin ni’ima (raƙuma da shanu da tumaki) da amfaninsu ga mutane.
• Ishara zuwa ga ƙissar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ruwan Ɗufana.
• Magana game da aiko manzanni zuwa ga mutanensu domin su kirawo su zuwa ga Tauhidi da bautar Allah; da bayanin yadda mutanensu suka ƙaryata su da abin da ya biyo bayan haka na uƙubar Allah gare su.
• Faɗakar da mushirikai a kan cewa su ma abin da suke nuna wa Annabi (ﷺ) na izgili da ƙaryatawa daidai yake da abin da waɗancan al’ummu suka nuna wa manzanninsu Allah kuma ya hallaka su, don haka su ma Allah yana iya yi musu hakan.

• Bayani a kan cewa mushirikai sun yarda da Kaɗaitakar Allah wajen halitta da sauran ayyukansa, amma kuma ba su yarda su kaɗaita shi da bauta ba. An nuna musu cewa tabbas za su yi nadama a kan haka lokacin da mutuwarsu ta zo da kuma a ranar alƙiyama.
• Bayani a kan cewa mushirikai sun san gaskiyar Annabi (ﷺ) sarai da amanarsa da kuma kasancewarsa mai yi musu nasiha don Allah ba don neman wani abu na duniya ba, don haka ba su da wani uzuri a gaban Allah game da shirkar da suka yi da ƙaryata Manzonsa, domin son zuciyarsu kaɗai suka bi.
• Daga ƙarshe Surar ta yi kira ga Annabi (ﷺ) da ya kau da kansa daga mummunar mu'amala da mushirikai suke yi masa, shi ya yi musu mafi kyawun mu'amala ya kuma roƙa wa muminai gafarar Allah.

Suratul Mu'uminun (1-11)

قَدۡ أَفۡلَحَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١ ٱلَّذِينَ هُمۡ فِي صَلَاتِهِمۡ خَٰشِعُونَ ٢ وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَنِ ٱللَّغۡوِ مُعۡرِضُونَ ٣ وَٱلَّذِينَ هُمۡ لِلزَّكَوٰةِ فَٰعِلُونَ ٤ وَٱلَّذِينَ هُمۡ
لِفُرُوجِهِمۡ حَٰفِظُونَ ٥ إِلَّا عَلَىٰٓ أَزۡوَٰجِهِمۡ أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُمۡ فَإِنَّهُمۡ غَيۡرُ مَلُومِينَ ٦ فَمَنِ ٱبۡتَغَىٰ وَرَآءَ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡعَادُونَ ٧ وَٱلَّذِينَ
هُمۡ لِأَمَٰنَٰتِهِمۡ وَعَهۡدِهِمۡ رَٰعُونَ ٨ وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَلَىٰ صَلَوَٰتِهِمۡ يُحَافِظُونَ ٩ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡوَٰرِثُونَ ١٠ ٱلَّذِينَ يَرِثُونَ ٱلۡفِرۡدَوۡسَ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١١

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Haƙiƙa muminai sun rabauta.

2. (Su ne) waɗanda suke masu ƙasƙantar da kai a cikin sallarsu.

3. Kuma waɗanda suke masu kau da kai daga yasasshiyar magana.

4. Kuma waɗanda suke masu aiwatar da zakka.

5. Kuma waɗanda suke masu kiyaye farjinsu.

6. Sai dai ga matayensu ko kuma ƙwara-ƙwaransu, to lalle su ba abin zargi ba ne.

7. Sannan duk wanda ya nemi (wata hanya) ba waɗannan ba, to waɗannan su ne masu ƙetare iyaka.

8. Kuma waɗanda suke masu kiyaye amanarsu da kuma alƙawarinsu.

9. Kuma waɗanda suke kiyaye sallolinsu.

10. Waɗannan su ne magada.

11. Waɗanda suke gadar (Aljannar) Firdausi, su madawwama ne a cikinta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da muminai samun rabauta a duniya da lahira, watau za su sami abin da suke burin samu na jin daɗin duniya da lahira, za kuma su kubuta daga duk wani abin ƙi ko ban tsoro.
Bayan babbar sifa ta imani da Allah ya kira muminai da ita, sai kuma ya siffanta su da wasu siffofi guda shida, su ne:
Ta farko, su ne masu ƙasƙantar da kai da nutsuwa a cikin sallarsu, gaɓoɓinsu sukan nutsu; ba sa bijiro wa zukatansu da abubuwan da za su shagaltar da su daga sallarsu.

Ta biyu, su ne masu kauce wa duk wata maganar banza ko aikin banza waɗanda suke ƙunshe da saɓon Allah, ko kuma marar amfani ga bawa duniya da lahira.
Ta uku, su ne masu tsarkake kawunansu daga dukkan wasu miyagun ayyuka, kuma suna tsarkake dukiyoyinsu ta hanyar sadaka ko fitar da zakka.
Ta huɗu, su ne masu kiyaye kawunansu daga aikata zina ko luwaɗi; a koyaushe suna tsare mutuncinsu, ba sa kusantar matan da ba su halatta a gare su ba, suna tsayawa ne kaɗai a kan matansu na aure ko saɗakunsu, to su waɗannan ba abin zargi ba ne don sun biya buƙatarsu a wajensu domin Allah ne ya halatta musu kusantar su. Sai Allah ya ƙara tabbatar da cewa duk wanda ya nemi biyan buƙatarsa ta wata hanya ba waɗannan ba, to wannan ya ƙetare iyaka ta Ubangiji.
Ta biyar, su ne masu kiyaye amanar da ke tsakaninsu da Allah da wadda take tsakaninsu da ‘yan’uwansu bayin Allah, ba sa cin amanar da take kansu. Hakanan suna kula da duk wata yarjejeniya da za a ƙulla da su, suna sauke nauyinsu ba tare da sun karya ta ba.
Ta shida, su ne masu kiyaye sallolinsu na farilla, suna yin su a kai-a kai tare da suna kula da lokutansu da rukunansu da wajibansu har ma da mustahabbai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa: Ya Manzon Allah, wanne aiki ne Allah ya fi so? Sai ya ce: “Yin salla a kan lokacinta.” Sai na ce: “Sannan wanne?” Sai ya ce: “Biyayya ga iyaye.” Sai na ce: “Sannan wanne?” Sai ya ce: “Jihadi a tafarkin Allah.” [Bukhari #5970 da Muslim #85].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci sakamakon da ya tanadar wa waɗannan muminai a ranar alƙiyama, da cewa su ne waɗanda za su gaji Aljannar Firdausi wadda ita ce mafi ɗaukakar gidan Aljanna, za su kuma dawwama a cikinta har abada cikin ni’imar da ba ta yankewa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan za ku roƙi Allah Aljanna to ku roƙe shi Aljannar Firdausi domin ita ce mafi ƙololuwar Aljanna, mafi darajar Aljanna; daga cikinta ne ƙoramun Aljanna suke ɓuɓɓugowa, a samanta kuma Al’arshin Allah Mai rahama yake.” [Bukhari #2790].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Babu wani daga cikinku face yana da gida biyu; gida a Aljanna da kuma gida a wuta; to idan ya mutu ya shiga wuta sai ‘yan Aljanna su gaje gidansa na Aljanna, wannan ita ce faɗar Allah: “Waɗannan su ne magada.” [Ibn Majah #4341].

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci Aljanna da tubalin zinare da na azurfa, ya kuma shuke ta, sannan ya ce mata: “Yi magana.” Sai ta ce: “Haƙiƙa muminai sun rabauta.” Sai mala’iku suka shiga cikinta suka ce: “Kin ji daɗinki, kin zama masaukin sarakuna.” [Albazzar, dubi *Kashful Astar* #3507].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ƙafa hujja da Kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wajen halittar ɗan’adam da ke nuna Kudurarsa a kan cewa zai iya tayar da shi bayan mutuwarsa.

2. Tabbatar wa da ɗan’adam cewa shi ba komai ba ne, bawan Allah ne, musamman idan zai dubi asalinsa.

3. Bayyana wa mutane ni’imar da Allah ya yi musu da ya fito da su daga babu zuwa ga samuwa, ta haka ne bambanci tsakanin muminai da kafirai zai fito fili. Muminai sun yi imani da hakan sun kuma tsaya da bautar Ubangijinsu, yayin da su kuma kafirai suka bijire masa suka ƙaryata manzanninsa ba tare da wata hujja ba.

4. Bayanin asalin mutum. Saɓanin ra’ayin masu cewa asalinsa biri ne ko wata halitta daban. Yarda da haka kuwa kafirci ne.

5. Tayar da matattu domin yi musu hisabi a ranar alƙiyama, abin da mushirikai da masu cewa babu Allah ba su yarda da shi ba.

Suratul Mu’uminun (12-16)
وَلَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ مِن سُلَٰلَةٖ مِّن طِينٖ ١٢ ثُمَّ جَعَلۡنَٰهُ نُطۡفَةٗ فِي قَرَارٖ مَّكِينٖ ١٣ ثُمَّ خَلَقۡنَا ٱلنُّطۡفَةَ عَلَقَةٗ فَخَلَقۡنَا ٱلۡعَلَقَةَ مُضۡغَةٗ فَخَلَقۡنَا ٱلۡمُضۡغَةَ عِظَٰمٗا فَكَسَوۡنَا ٱلۡعِظَٰمَ لَحۡمٗا ثُمَّ أَنشَأۡنَٰهُ خَلۡقًا ءَاخَرَۚ فَتَبَارَكَ ٱللَّهُ أَحۡسَنُ ٱلۡخَٰلِقِينَ ١٤ ثُمَّ إِنَّكُم بَعۡدَ ذَٰلِكَ لَمَيِّتُونَ ١٥ ثُمَّ إِنَّكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ تُبۡعَثُونَ ١٦

12. Kuma haƙiƙa Mun halicci mutum daga tataccen taɓo.

13. Sannan Muka mai da shi maniyyi cikin wuri amintacce.

14. Sannan Muka mayar da maniyyin ya zama gudan jini, sai gudan jinin ya zama tsoka, sai Muka mai da tsokar ƙasusuwa, sannan Muka lulluɓe ƙasusuwan da nama, sannan kuma Muka mai da shi wata halitta daban. To albarkatun Allah sun yawaita,Wanda Shi ne Mafi gwanintar masu halitta.

15. Sannan kuma lalle tabbas bayan haka za ku mutu.

16. Sannan kuma haƙiƙa za a tashe ku ranar alƙiyama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana asalin halittar ɗan’adam na farko, watau Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya halicce shi da yumɓu, wanda aka ɗebo tatacciyar ƙasarsa da ta gauraya da ruwa. Sannan kuma Allah ya halicci zurriyyarsa masu hayayyafa ta hanyar ɗigon maniyyi da yake sauka cikin mahaifa ya tabbata cikinta har zuwa lokacin haihuwa. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa daga wannan ɗigon maniyyin ne ya halicci wani gudan jini, sannan ya halicci wata tsokar nama wadda take gwargwadon loma daga wannan gudan jinin, sannan kuma daga wannan tsokar ya halicci ƙasusuwa masu ƙarfi, sai kuma ya lulluɓe waɗannan ƙasusuwa da nama, sannan sai ya mayar da shi wata halitta daban ta hanyar busa masa rai da fito da shi duniya. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa kansa kirari da cewa, albarkatunsa sun yawaita, kuma shi ne mafi gwanintar masu halitta.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah mai gaskiya abin gaskatawa ya faɗa mana cewa: “Lalle ɗayanku ana tattara halittarsa a cikin mahaifiyarsa kwana arba’in (watau yana maniyyi), sannan ya zama jini kwatankwacin haka, sannan ya zama tsoka kamar haka, sannan Allah ya aiko wani mala’ika ya ba shi umarni guda huɗu, a ce masa, rubuta aikinsa da arziƙinsa da ajalinsa, ɗan wuta ne shi ko ɗan Aljanna, sannan a busa masa rai....” [Bukhari #3208 da Muslim #2643].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle Allah mai girma da buwaya ya wakilta wa mahaifa wani mala’ika yana cewa: “Ya Ubangijina maniyyi ne, ya Ubangijina gudan

jini ne, ya Ubangijina gudar tsoka ce." Idan Allah ya nufi ya cika halittarsa, sai mala'ikan ya tambaya cewa: Namiji ne shi ko mace? Ɗan wuta ne shi ko ɗan Aljanna? Kuma mene ne arziƙinsa da ajalinsa? Sai duk a rubuta su yana cikin mahaifiyarsa." [Bukhari #318 da Muslim #2646].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutane cewa bayan duk sun gama bin waɗannan matakan halitta, to za su kuma mutu yayin da ajalinsu ya zo, sannan kuma bayan mutuwa tabbas za a tashe su daga ƙaburburansu a ranar alƙiyama domin a yi musu hisabi a kan ayyukansu masu kyau da marasa kyau.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ilimin Allah ya kewaye dukkan halittunsa.

2. Allah mai tausaya wa halittunsa ne, don haka yake saukar musu da ruwan sama gwargwadon buƙatarsu; ba mai ɓarna ba kuma ba marar wadatarwa ba.

3. Bayanin matsayin itaciyar dabino da ta inabi don yawan amfanin da ke tattare da su.

4. Bayanin amfanin bishiyar zaitun.

Suratul Mu'uminun (17-20)
وَلَقَدۡ خَلَقۡنَا فَوۡقَكُمۡ سَبۡعَ طَرَآئِقَ وَمَا كُنَّا عَنِ ٱلۡخَلۡقِ غَٰفِلِينَ ١٧ وَأَنزَلۡنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءَۢ بِقَدَرٖ فَأَسۡكَنَّٰهُ فِي ٱلۡأَرۡضِۖ وَإِنَّا عَلَىٰ ذَهَابِۭ بِهِۦ لَقَٰدِرُونَ ١٨ فَأَنشَأۡنَا لَكُم بِهِۦ جَنَّٰتٖ مِّن نَّخِيلٖ وَأَعۡنَٰبٖ لَّكُمۡ فِيهَا فَوَٰكِهُ كَثِيرَةٞ وَمِنۡهَا تَأۡكُلُونَ ١٩ وَشَجَرَةٗ تَخۡرُجُ مِن طُورِ سَيۡنَآءَ تَنۢبُتُ بِٱلدُّهۡنِ وَصِبۡغٖ لِّلۡأٓكِلِينَ ٢٠

17. Kuma haƙiƙa Mun halicci hanyoyi bakwai a sama da ku, ba Mu kuma zama gafalallu ba game da halittar.

18. Muka kuma saukar da ruwa daga sama daidai gwargwado, sai Muka zaunar da shi a cikin ƙasa, kuma lalle Mu Masu iko ne a kan kawar da shi.

19. Sai Muka samar muku gonaki na dabinai da inabai da shi (ruwan), kuna kuma da kayan marmari masu yawa a cikinsu (gonakin), kuma daga gare su kuke ci.

20. Kuma (Mun halitta muku) wata bishiya da take fitowa a (dutsen) Ɗuri Sina'a, tana fito da man (zaitun) kuma mahaɗin abinci ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu dalilai masu nuna ƙarfin ikonsa da cikar Kudurarsa a kan aikata abin da ya ga dama, daga cikinsu har da rayar da matattu. Ya bayyana wa mutane cewa shi ne ya halicci sammai bakwai a samansu, kuma yana sane da komai da ya halitta, bai zama mai gafala game da su ba ko mai mantuwa.
Sannan kuma shi ne ya saukar da ruwan sama gwargwadon buƙata, bai yi yawan da zai haddasa ɓarna ba, bai kuma yi kaɗan ba har ya kasa isa, Allah kuma ya tabbatar da shi a kan ƙasa domin mutane su amfana da shi, su sha su shayar da dabbobinsu. Sannan ya tabbatar musu cewa yana da ikon ya tafiyar da shi daga doron ƙasa ba tare da sun amfana da shi ba. Kuma da wannan ruwa ne ya fitar musu da gonaki na itatuwan dabino da na inabi. Baya ga wannan gonakin suna cike da kayan marmari iri-iri kamar ɓaure da rumman da tuffa waɗanda suke ci idan sun yi marmari.

Har wa yau da wannan ruwan ne dai ya fitar musu da itaciyar zaitun wadda take fitowa a yankin dutsen Ɗuri Sina'a; a jikinta ake samun man zaitun wanda ake shafawa kuma ana haɗa miyar abinci da shi.
Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wata halitta da ke rayuwa tare da ɗan'adam tana ɗauke da ayoyi da hujjoji iri-iri masu nuna Ɗayantakar Allah. Ciki har da dabbobin da yake amfani da su yau da kullum yana hawan su yana cin namansu yana amfana da su ta hanyoyi daban-daban. Dukkansu ayoyi ne fal tare da su ga ɗan'adam.

2. Halaccin hawa jiragen ruwa da safara a kansu. Wannan kuma yana nuna har ila yau halaccin hawa jiragen sama da na ƙasa duk kuwa da girman hatsarin da ke tattare da su, domin haɗarin da ke cikin hawa jirgin ruwa ba zai kasa na jirgin sama ba in ma bai fi shi ba.

Suratul Mu'uminun (21-22)
وَإِنَّ لَكُمۡ فِي ٱلۡأَنۡعَٰمِ لَعِبۡرَةٗۖ نُّسۡقِيكُم مِّمَّا فِي بُطُونِهَا وَلَكُمۡ فِيهَا مَنَٰفِعُ كَثِيرَةٞ وَمِنۡهَا تَأۡكُلُونَ ٢١ وَعَلَيۡهَا وَعَلَى ٱلۡفُلۡكِ تُحۡمَلُونَ ٢٢

21. Kuma lalle akwai izina a gare ku game da dabbobin ni'ima; Muna shayar da ku daga abin da yake cikinsu, kuma kuna da amfani mai yawa daga gare su, daga gare su kuma kuke ci.

22. A kansu da kuma a kan jirgin ruwa ake ɗaukar ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana dalilan Kudurarsa da cikar ikonsa, da cewa, a tare da dabbobin ni'ima, watau raƙuma da shanu da tumaki da awaki, akwai izina da ƙarfafan dalilai masu nuna ƙarfin Kudurar Allah da tausayawarsa gare su, ya kuma bayyana musu cewa yana shayar da su tataccen nono daga abin da yake cikinsu mai daɗin kwankwaɗa ga masu sha, sannan kuma suna samun amfani mai yawa daga waɗannan dabbobi, kamar na hawa da ɗora musu kaya da amfani da gashinsu da fatunsu, sannan kuma su ci namansu. Haka kuma a tafiye-tafiyensu a kan ƙasa suna hawan irin su raƙuma, a ruwa kuwa su hau jiragen ruwa tare da kayayyakinsu na fatauci. Watau dai ya kamata su fahimci cewa wanda ya yi musu waɗannan ni'imomi daban-daban lalle ya cancanci godiya da yabo, ya kuma cancanci a bauta masa shi kaɗai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da annabcin Annabi Muhammadu (ﷺ) ta hanyar ba shi labarin gaibu wanda ba zai iya sanin sa ba sai ta hanyar wahayi.

2. Bayanin cewa dukkan annabawan Allah da suka gabaci Annabi (ﷺ) sun zo ne da kira zuwa ga Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta da watsi da shirka, watau bautar wani tare da Allah.

3. Farkon waɗanda suke fitowa suna faɗa da annabawa da masu ƙoƙarin kawo gyara cikin al'umma su ne manyan gari waɗanda suka kafirce wa Allah.

4. Babban ruɗanin kafirai a kan ƙaryata manzancin manzanni shi ne wai su mutane ne kamarsu, wai me ya hana a aiko musu da mala'iku. Wannan kuwa mummunan jahilci ne da rashin gane hikimar Allah ta aiko wa mutane 'yan'uwansu mutane, domin babu yadda za su iya tunkarar mala'iku har su yi magana da su; don haka ko da mala'ika Allah ya aiko to sai ya mayar da shi mai surar mutum, idan kuma ya yi haka to su kuma za su ƙara rikicewa su ce ba mala'ika ne ba mutum ne irinsu.

5. Babu tufka da warwara da ƙarancin tunani kamar na mutanen da suka yarda dutse ya zame musu alla abin bauta, amma kuma suna jayayya a kan mutum ya zama Manzon Allah.

6. Tsohuwar al'ada ce ta azzalumai a kowane zamani su riƙa tuhumar masu wa'azi da kawo gyara cikin al'umma da abubuwan da suka yi hannun riga da su, kamar hauka da ƙarya da makamancin haka.

7. Bayanin yadda Allah yake taimaka wa manzanninsa idan sun nemi hakan daga gare shi.

8. Wajabcin yi wa Allah godiya a kan ni'imar da ya yi wa bawa da yabon sa a kanta.

Suratul Mu'uminun (23-30)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ فَقَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥٓۚ أَفَلَا تَتَّقُونَ ٢٣ فَقَالَ ٱلۡمَلَؤُاْ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَوۡمِهِۦ مَا هَٰذَآ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ يُرِيدُ أَن يَتَفَضَّلَ عَلَيۡكُمۡۚ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَأَنزَلَ مَلَٰٓئِكَةٗ مَّا سَمِعۡنَا بِهَٰذَا فِيٓ ءَابَآئِنَا ٱلۡأَوَّلِينَ ٢٤ إِنۡ هُوَ إِلَّا رَجُلُۢ بِهِۦ جِنَّةٞ فَتَرَبَّصُواْ بِهِۦ حَتَّىٰ حِينٖ ٢٥ قَالَ رَبِّ ٱنصُرۡنِي بِمَا كَذَّبُونِ ٢٦ فَأَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡهِ أَنِ ٱصۡنَعِ ٱلۡفُلۡكَ بِأَعۡيُنِنَا وَوَحۡيِنَا فَإِذَا جَآءَ أَمۡرُنَا وَفَارَ ٱلتَّنُّورُ فَٱسۡلُكۡ فِيهَا مِن كُلّٖ زَوۡجَيۡنِ ٱثۡنَيۡنِ وَأَهۡلَكَ إِلَّا مَن سَبَقَ عَلَيۡهِ ٱلۡقَوۡلُ مِنۡهُمۡۖ وَلَا تُخَٰطِبۡنِي فِي ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْۚ إِنَّهُم مُّغۡرَقُونَ ٢٧ فَإِذَا ٱسۡتَوَيۡتَ أَنتَ وَمَن مَّعَكَ عَلَى ٱلۡفُلۡكِ فَقُلِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي نَجَّىٰنَا مِنَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٨ وَقُل رَّبِّ أَنزِلۡنِي مُنزَلٗا مُّبَارَكٗا وَأَنتَ خَيۡرُ ٱلۡمُنزِلِينَ ٢٩ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ وَإِن كُنَّا لَمُبۡتَلِينَ ٣٠

23. Haƙiƙa kuma Mun aiko Nuhu zuwa ga mutanensa, sai ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta in ba Shi ba; me ya sa ne ba za ku yi taƙawa ba."

24. Sai manya-manyan da suka kafirce daga mutanen nasa suka ce: "Ai wannan ba kowa ba ne face mutum irinku, yana so ne ya samu fifiko a kanku, kuma da Allah Ya ga dama da sai Ya saukar da mala'iku, mu ba mu taɓa jin irin wannan ba daga iyayenmu na farko.

25. "Ba kowa ba ne shi in ban da mutum da yake da (taɓin) aljan, sai ku saurara masa har zuwa wani ɗan lokaci."

26. Ya ce: "Ubangijina Ka taimake ni game da abin da suka ƙaryata ni a kansa."

27. Sai Muka yiwo masa wahayi cewa: "Ka sassaƙa jirgin ruwa a ƙarƙashin kulawarmu da umarninmu, sannan idan umarninmu (na hallaka su) ya zo, kuma tanderu ya ɓuɓbugo da ruwa, sai ka saka ma'aurata guda biyu daga kowane jinsi a cikinsa, da kuma iyalanka, sai wanda kalmar (halaka) ta rigaya a kansa daga cikinsu; kuma kada ka ce min komai game da waɗanda suka kafirta; lalle su waɗanda za a nutsar ne.

28. "To idan kai da waɗanda suke tare da kai kuka daidaita a kan jirgin, sai ka ce: "Na gode wa Allah wanda Ya tserar da mu daga mutane azzalumai."

29. Kuma ka ce: "Ubangijina Ka saukar da ni masauki mai albarka, Kai ne kuwa Fiyayyen masu saukarwa."

30. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi, Mu kuma haƙiƙa Mun kasance Masu jarrabawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya aika Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga mutanensa domin ya kirawo su zuwa ga Allah, ya umarce su da su bauta wa

Allah shi kaɗai kuma ba su da wani abin bauta na gaskiya sai shi kaɗai, ya nuna musu cewa yanzu ba sa kiyaye dokokin Allah ba, su bi umarninsa su guji haninsa?
Amma sai manya-manyan garin waɗanda suka kafirce wa Allah daga cikin mutanensa suka fito suna hure wa mabiyansu kunne, suna nuna musu cewa Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) fa ba wani ba ne, shi ma mutum ne irinsu, kuma wannan wa'azi da yake yi musu ba wani abu yake so ba illa kawai ya shugabance su ya mayar da su ƙarƙashinsa sai yadda ya ce. Suka nuna musu cewa da Allah ya ga damar aiko da wani manzo to da sai ya aiko da mala'ika ba mutum ba irinsu. Sannan suka nuna musu cewa wannan abu da ya zo da shi ba su taɓa jin labarin wani abu mai kama da shi ba a wajen iyayensu na farko. Ba su tsaya iya nan ba, sai da suka kai ga tuhumar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da hauka da ma rashin sanin abin da yake faɗa. Sannan suka kirawo mutane cewa su zura masa ido har zuwa lokacin da asirinsa zai tonu, ko kuma ya mutu ƙowa ya huta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ɗaga hannu ya roƙe shi cewa ya kawo masa agaji da taimako a kan mutanensam saboda sun ƙaryata shi, bayan ya ɗauki dogon lokaci yana yi musu wa'azi ba dare ba rana har shekara dubu ba hamsin amma 'yan kaɗan ne ƙwarai suka yi imani da shi a cikinsu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa wahayi da ya sassaƙa jirgin ruwa a ƙarƙashin kulawarsa (Mai tsarki da ɗaukaka) da koyarwarsa gare shi yadda zai yi sassaƙar. Allah kuma ya sanar da shi cewa idan umarninsa na hallaka mutanensa ya zo masa ya kuma ga ruwa ya fara ɓuɓɓugowa daga cikin tanderu, to ya yi hanzari ya ɗauki namiji da mace daga duk wani abu mai rai don su ci gaba da hayayyafa, ya kuma haɗa har iyalansa cikin wannan jirgin in ban da wanda kalmar hallaka ta riga ta tabbata a kansa, watau matarsa da ɗansa. Sannan Allah ya yi masa kashedi da kada ya kuskura ya yi masa magana a kan waɗanda suka kafirta ya nemi a kuɓutar da su. Su waɗannan Allah ya tabbatar masa za a nutsar da su ne a cikin wannan ruwa na Ɗufana.
Sai kuma ya koyar da shi abin da zai faɗa shi da waɗanda ya ɗauko a cikin wannan jirgin bayan sun hau sun daidaita a kansa, da cewa: "Yabo da godiya sun tabbata ga Allah wanda ya tserar da mu daga mutane azzalumai." Sannan ya roƙi Allah Ubangijinsa ya saukar da shi masauki mai albarka a bayan ƙasa, domin Allah shi ne fiyayyen masu ba da masauki.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a cikin wannan aiki nasa na tserar da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da muminai da hallaka kafirai a cikin ruwa lalle akwai hujjoji bayyanannu da suke nuna Kudurar Allah wajen taimakon manzanninsa da hallaka masu ƙaryata su. Ya kuma tabbatar da cewa lalle ya jarrabi mutanen Annabi Nuhu da aiko musu shi da ya yi domin a tantance mumini da kafiri, mai biyayya da bijirarre.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jin daɗi idan ya yi yawa yana daga cikin abubuwan da suke janyo gafala da girman kai na ƙin gaskiya.

2. Sau da yawa kafirai sun yi ta kafa hujja a kan ƙaryata manzanni da zamantowarsu mutane.

3. Annabawa da manzanni mutane ne waɗanda kuma suke da siffofin mutuntaka, kamar ci da sha da rashin lafiya.

4. Al'ada ce daɗaɗɗiya ta marasa gaskiya su riƙa jifan masu ƙokarin kawo gyara cikin al'umma da tuhumce-tuhumce na ƙarya, su riƙa jifan su da miyagun sunaye.

5. Allah yakan amsa addu'ar waɗanda aka zalunta, musamman idan sun kasance bayinsa ne na gari.

6. Zalunci yana daga cikin abubuwan da suke nesanta bawa daga rahamar Allah.

Suratul Mu’uminun (31-41)

ثُمَّ أَنشَأۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِمۡ قَرۡنًا ءَاخَرِينَ ٣١ فَأَرۡسَلۡنَا فِيهِمۡ رَسُولًا مِّنۡهُمۡ أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥٓۚ أَفَلَا تَتَّقُونَ ٣٢ وَقَالَ ٱلۡمَلَأُ مِن قَوۡمِهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِلِقَآءِ ٱلۡأٓخِرَةِ وَأَتۡرَفۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا مَا هَٰذَآ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ يَأۡكُلُ مِمَّا تَأۡكُلُونَ مِنۡهُ وَيَشۡرَبُ مِمَّا تَشۡرَبُونَ ٣٣ وَلَئِنۡ أَطَعۡتُم بَشَرٗا مِّثۡلَكُمۡ إِنَّكُمۡ إِذٗا لَّخَٰسِرُونَ ٣٤ أَيَعِدُكُمۡ أَنَّكُمۡ إِذَا مِتُّمۡ وَكُنتُمۡ تُرَابٗا وَعِظَٰمًا أَنَّكُم مُّخۡرَجُونَ ٣٥ ۞هَيۡهَاتَ هَيۡهَاتَ لِمَا تُوعَدُونَ ٣٦ إِنۡ هِيَ إِلَّا حَيَاتُنَا ٱلدُّنۡيَا نَمُوتُ وَنَحۡيَا وَمَا نَحۡنُ بِمَبۡعُوثِينَ ٣٧ إِنۡ هُوَ إِلَّا رَجُلٌ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبٗا وَمَا نَحۡنُ لَهُۥ بِمُؤۡمِنِينَ ٣٨ قَالَ رَبِّ ٱنصُرۡنِي بِمَا كَذَّبُونِ ٣٩ قَالَ عَمَّا قَلِيلٖ لَّيُصۡبِحُنَّ نَٰدِمِينَ ٤٠ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلصَّيۡحَةُ بِٱلۡحَقِّ فَجَعَلۡنَٰهُمۡ غُثَآءٗۚ فَبُعۡدٗا لِّلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٤١

31. Sannan kuma a bayansu Muka halicci wata al’umma daban.

32. Sai Muka aiko musu wani manzon daga cikinsu da cewa: “Ku bauta wa Allah, ba ku da wani abin bauta in ba Shi ba; me ya sa ne ba za ku yi taƙawa ba?”

33. Kuma manyan mutane daga cikin mutanensa waɗanda suka kafirce suka kuma ƙaryata haɗuwa da ranar lahira, Muka kuma wadata su a rayuwar duniya, suka ce: “Wannan ba kowa ba ne face mutum kamarku, yana cin irin abin da kuke ci, yana kuma shan irin abin da kuke sha.

34. “Kuma tabbas in har kuka bi mutum kamarku, to lalle tabbas a sannan kun yi asara.

35. “Shin yanzu ya riƙa yi muku alƙawarin cewa idan kun mutu kun kuma zama turɓaya da ƙasusuwa cewa lalle za a tashe ku?”

36. “Faufau-faufau game da abin da ake yi muku alƙawarinsa!

37. “Ba mu da wata (rayuwa) sai rayuwarmu ta duniya; mu mutu kuma mu rayu, ba kuwa za a tashe mu (daga ƙaburburanmu) ba.

38. “Shi ba kowa ba ne face mutum da ya ƙaga wa Allah ƙarya, mu kuwa ba za mu yi imani da shi ba.”

39. Ya ce: “Ya Ubangijina, Ka taimake ni game da abin da suke ƙaryata ni a kansa.”

40. Ya ce: “Ba da daɗewa ba tabbas za su wayi gari suna masu nadama.”

41. Sai tsawa ta far musu bisa cancanta, sai Muka mai da su dudduga. To nisanta (daga rahamar Allah) ta tabbata ga mutane azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan ya hallakar da mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kuma samar da wata al’umma daban, ita ma ya aiko mata da wani manzo wanda ya kirawo su zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, kuma su ji tsoron Allah su kiyaye dokokinsa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, manya masu faɗa a ji daga cikin mutanensa waɗanda suka kafirce wa Allah suka ƙaryata zuwan ranar lahira da abin da yake cikinta na sakamako da uƙuba, kuma har ila yau abin da suke rayuwa a cikinsa na jin daɗin duniya da arziƙi da Allah ya ba su ya ƙara musu

ɗagawa da girman kai, sai suka fito suna faɗa wa mabiyansu cewa kada su saurari wannan manzon da abin da yake faɗa musu, domin shi ba kowa ba ne face mutum kamarsu, yana cin irin abincin da suke ci yana shan irin abin da suke sha, don haka bai fi su da komai ba balle ma har a ce an naɗa shi manzo an aiko shi wajensu. Suka yi musu kashedi da cewa idan har suka kuskura suka bi shi suka yarda da shi bayan shi mutum ne kamarsu, to lalle sun tabbata hasararru, domin babu wata tsiya da zai tsinana musu, ga shi kuma sun bar bautar allolinsu.
Suka ci gaba da nuna wa mabiyansu cewa, wannan da yake cewa shi manzo ne yana faɗa musu abin da hankalinsu ba zai taɓa gamsuwa da shi ba. Ta ƙaƙa zai riƙa yi musu alƙawarin cewa idan sun mutu sun ratattake sun zama ƙasa da ƙasusuwa rududdugaggu, wai za a sake tayar da su da rai? Suka nuna cewa sam-sam wannan batu ba zai taɓa zama gaskiya ba, don haka alƙawarin da yake yi musu ƙanzon kurege ne kawai.
Suka hure musu kunnuwa da cewa babu wata rayuwa bayan ta duniya, masu rai daga cikinsu idan sun mutu to ba za a ƙara tashin su ba, waɗanda kuma aka haifa su ne za su ci gaba da rayuwa, kuma ba za a fito da su ba a yi musu hisabi bayan mutuwarsu.
Sannan suka tuhume shi da cewa shi kawai mutum ne da ya ƙirƙira wa Allah ƙarya ya ce aiko shi ya yi, alhalin ba haka ne ba, don haka suka tabbatar da cewa su ba za su yi imani da shi ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da lamarin ya kai haka sai wannan manzo ya roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya taimake shi ya hallakar da waɗannan mutane da suka ƙaryata shi. Allah kuwa ya amsa masa da cewa ba da daɗewa ba hallaka za ta zo musu, su wayi gari suna nadama a kan abin da suka aikata lokacin kuma da nadamar ba za ta amfane su da komai ba. Haka kuwa aka yi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da wata tsawa mai tsananin gaske ta hallaka su bisa cancanta, don haka suka wayi gari sun zama kamar duddugar ruwa. Allah ya bayyana cewa nisantar rahama ta tabbata ga waɗannan azzalumai.
Wasu malamai sun ce waɗannan mutane su ne Samudawa mutanen Annabi Salihu, domin su ne waɗanda Allah ya hallakar da su da tsawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kamar yadda ɗaiɗaikun mutane kowa yake da ajalinsa wanda ba ya gaza shi, ba kuma ya tsallake shi, to haka su ma al'ummu suke, kowace al'umma da nata ajalin wanda ba za ta ƙetare shi ba.

2. Karyata annabawa da manzanni da mutanen kirki wata sunnar Allah ce a rayuwar ɗan'adam.

Suratul Mu'uminun (42-44)
ثُمَّ أَنشَأۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِمۡ قُرُونًا ءَاخَرِينَ ٤٢ مَا تَسۡبِقُ مِنۡ أُمَّةٍ أَجَلَهَا وَمَا يَسۡتَـٔۡخِرُونَ ٤٣ ثُمَّ أَرۡسَلۡنَا رُسُلَنَا تَتۡرَاۖ كُلَّ مَا جَآءَ أُمَّةً رَّسُولُهَا كَذَّبُوهُۖ فَأَتۡبَعۡنَا بَعۡضَهُم بَعۡضٗا وَجَعَلۡنَٰهُمۡ أَحَادِيثَۚ فَبُعۡدٗا لِّقَوۡمٖ لَّا يُؤۡمِنُونَ ٤٤

42. Sannan kuma a bayansu Muka halitta wasu al'ummun daban.

43. Babu wata al'umma da take rigayar ajalinta, babu kuma wadda take jinkiri.

44. Sannan Muka aiko manzanninmu suna biye da juna; duk sanda manzon (kowacce) al'umma ya zo musu sai su ƙaryata shi. Sai Muka hallaka su ɗaya bayan ɗaya, Muka kuma mai da su tarihi. To nisanta (daga rahamar Allah) ta tabbata ga mutanen da ba sa yin imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan ya hallaka wasu al'ummu da suka

ƙaryata annabawansu, ya sake tayar da wasu al'ummun daban kamar mutanen Annabi Luɗu da na Annabi Shu’aibu da na Annabi Yunus. A duk waɗannan al’ummu babu wata al’umma da za ta gabaci lokacin hallakarta, watau a hallakar da ita kafin lokacinta ya cika, ko kuma a jinkirta mata bayan wa’adinta ya yi. Watau da zarar lokacin hallaka su ya zo to sai a halaka su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya yi ta aiko manzanni ɗaya bayan ɗaya suna bibiyar juna, to amma abin takaicin duk sa’adda wani manzo ya zo ga mutanensa ya kirawo su zuwa ga kaɗaita Allah da bauta da nisantar bautar wanin Allah, sai wannan al’ummar su ƙaryata shi duk kuwa da irin ayoyi da mu’ujizoji da zai nuna musu. To wannan ya sa Allah ya riƙa hallaka su ɗaya bayan ɗaya har sai da aka wayi gari babu ko ɗaya daga cikinsu dukkansu sun zama tarihi, sai dai a ji labarinsu a bakin mutane, don haka hallaka ta tabbata ga mutanen da suka ƙi yin imani da abin da manzanninsu suka zo musu da shi daga Ubangijinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman kai da nuna isa suna daga cikin sabubban bijire wa gaskiya da wulaƙanta mutane.

2. Mutanen Fir’auna sun kafa hujja a kan bijire wa da’awar Annabi Musa da Haruna da zamantowarsu mutane ne kamar su.

3. Shiriyar Allah tana tattare ne a cikin aiki da littafin Allah.

Suratul Mu’uminun (45-49)
ثُمَّ أَرۡسَلۡنَا مُوسَىٰ وَأَخَاهُ هَٰرُونَ بِـَٔايَٰتِنَا وَسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٍ ٤٥ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَإِيْهِۦ فَٱسۡتَكۡبَرُواْ وَكَانُواْ قَوۡمًا عَالِينَ ٤٦ فَقَالُوٓاْ أَنُؤۡمِنُ لِبَشَرَيۡنِ مِثۡلِنَا وَقَوۡمُهُمَا لَنَا عَٰبِدُونَ ٤٧ فَكَذَّبُوهُمَا فَكَانُواْ مِنَ ٱلۡمُهۡلَكِينَ ٤٨ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ لَعَلَّهُمۡ يَهۡتَدُونَ ٤٩

45. Sannan Muka aiko Musa da ɗan’uwansa Haruna da ayoyinmu da kuma hujja bayyananniya.

46. Zuwa ga Fir’auna da manyan ('yan majalisarsa), sai suka yi girman kai kuma suka kasance mutane masu haike wa (jama'a da zalaunci).

47. Sai suka ce: “Yanzu ma ba da gaskiya da mutum biyu irinmu, alhali kuwa mutanensu masu yi mana bauta ne?”

48. Sai suka ƙaryata su (wato Musa da Haruna), sannan suka kasance daga waɗanda aka hallaka.

49. Haƙiƙa kuma Mun bai wa Musa Littafi (wato Attaura) don su shiriya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya aiko Annabi Musa da Annabi Haruna da ayoyi masu nuna gaskiyar manzancinsu; ayoyin su ne: sanda da hannu mai haske da farin ɗango da ƙwarƙwata da kwaɗi da jini da ɗufana da fari da tawayar amfanin gona. Allah kuma ya ba su hujja bayyananna.
Allah ya aike su zuwa ga Fir’auna da manyan mutanensa, to amma sai suka yi girman kai suka ƙi ba da gaskiya da su. Allah ya tabbatar da cewa da man can mutane ne masu nuna ɗagawa ga sauran mutane da zalunci da cutarwa. Saboda nuna isarsu ma cewa suka yi, ta yaya ma za su yi imani da wasu mutane biyu, watau Musa da Haruna waɗanda su ma kamarsu suke ba su fi su da komai ba, sannan ga mutanensu,

watau Banu Isra’ila bayinsu ne a ƙarƙashinsu suke bauta. Don haka sai suka ƙaryata su, hakan kuma ya zama sanadiyyar hallaka su cikin kogi duk suka nutse.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan ya hallaka Fir’auna da rundunarsa ya kuma kuɓutar da Annabi Musa da mutanensa sai kuma ya ba shi littafin Attaura da fatan mutanensa su shiriya da shi su yi aiki da gaskiyar da ya ƙunsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haihuwar Annabi Isa ba tare da uba ba hujja ce mai tabbatar da cikar Kudurar Allah.

2. Cin halal yana da matuƙar tasiri wajen gyara zukata da ayyuka.

3. Duk manzanni sun haɗu a kan halatta tsarkakan abubuwa masu daɗin ci da haramta duk ƙazantattun abubuwa. Sun kuma haɗu a kan aikata duk wani aiki na gari kamar umarni da kaɗaita Allah da tsantsanta addini gare shi don nuna masa soyayya da tsoronsa da gaskiya da cika alƙawari da riƙe yarjejeniya da sada zumunci da biyayya ga iyaye da kyautata wa mabuƙata da marayu da sauransu.

4. Babu wata ƙungiya face tana ganin cewa abin da take kai shi ne tsantsar gaskiya, sannan abin da masu saɓa mata suke kai tsantsar ƙarya ne. Ma’auni na gaskiya dai shi ne dacewa da littafin Allah da abin da annabawa suka zo da shi.

5. Ci gaba na duniya ta fannin tattalin arziƙi da ƙere-ƙere ba shi ne yake nuna zaɓin Allah ga wannan al’umma ba. Yakan iya zama talala ce Allah yake yi don damƙarsa a gare su ta tsananta.

Suratul Mu’uminun (50-56)
وَجَعَلْنَا ٱبْنَ مَرْيَمَ وَأُمَّهُۥٓ ءَايَةً وَءَاوَيْنَٰهُمَآ إِلَىٰ رَبْوَةٍ ذَاتِ قَرَارٍ وَمَعِينٍ ﴿٥٠﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرُّسُلُ كُلُوا۟ مِنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَٱعْمَلُوا۟ صَٰلِحًا ۖ إِنِّى بِمَا تَعْمَلُونَ
عَلِيمٌ ﴿٥١﴾ وَإِنَّ هَٰذِهِۦٓ أُمَّتُكُمْ أُمَّةً وَٰحِدَةً وَأَنَا۠ رَبُّكُمْ فَٱتَّقُونِ ﴿٥٢﴾ فَتَقَطَّعُوٓا۟ أَمْرَهُم بَيْنَهُمْ زُبُرًا ۖ كُلُّ حِزْبٍۭ بِمَا لَدَيْهِمْ فَرِحُونَ ﴿٥٣﴾ فَذَرْهُمْ فِى
غَمْرَتِهِمْ حَتَّىٰ حِينٍ ﴿٥٤﴾ أَيَحْسَبُونَ أَنَّمَا نُمِدُّهُم بِهِۦ مِن مَّالٍ وَبَنِينَ ﴿٥٥﴾ نُسَارِعُ لَهُمْ فِى ٱلْخَيْرَٰتِ ۚ بَل لَّا يَشْعُرُونَ ﴿٥٦﴾

50. Muka kuma sanya Ɗan Maryamu da mahaifiyarsa (don su zama) aya, Muka kuma zaunar da su a wata jigawa ta hutawa da kuma ruwa mai gudana.

51. Ya ku manzanni, ku ci daga halal, kuma ku yi aiki na gari; Lalle Ni ina sane da abin da kuke aikatawa.

52. Kuma lalle wannan addininku ne, addini guda ɗaya (wato Musulunci), kuma Ni ne Ubangijinku, sai ku kiyaye dokokina.

53. Sai suka sassaɓa al’amarinsu a tsakaninsu (suka kasu) ƙungiya-ƙungiya; kowacce ƙungiya tana alfahari da nata.

54. Sai ka bar su cikin ɗimuwarsu har zuwa ɗan wani lokaci.

55. Yanzu suna tsammanin cewa abin da Muke ba su na dukiya da ‘ya’yaye (a duniya).

56. Muna gaggauto musu sakamakon alheri ne? Ba haka ba ne; su dai ba sa ganewa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya sanya Annabi Isa da mahaifiyarsa Maryamu su zama aya wadda take nuna cikar Kudurarsa ta ya halicci abin da ya ga dama, a yadda ya ga dama, don haka Nana Maryamu ta ɗauki cikin Annabi Isa ba tare da namiji ba. Allah ya bayyana cewa ya zaunar da Annabi Isa da mahaifiyarsa a kan wata jigawa ma'abociyar wurin hutu da nutsuwa, wadda kuma take da wani idon ruwa mai kwarara koyaushe.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci manzanni da cin halal mai daɗi da kuma yin ayyuka na gari waɗanda suka yi daidai da shari'a, ya kuma tabbatar musu da cewa yana sane da aikin kowa daga cikinsu kuma zai yi wa kowa sakayya a kan ayyukansa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya ku mutane, lalle Allah tsattsarka ne ba ya karɓar wani aiki sai tsarkakakke, kuma lalle Allah ya umarci muminai da abin da ya umarci manzanni da shi. Allah ya ce: "Ya ku manzanni, ku ci daga tsarkakan abubuwa na halal, kuma ku yi aiki na gari, lalle ni ina sane da abin da kuke aikatawa." Ya kuma ce: "Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ci daga tsarkakan abubuwa na halal da muka arzuta ku."… [Muslim #1015].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani annabi da bai yi kiwon dabbobi ba." Sahabbai suka ce: "Har kai ma ya Manzon Allah?" Ya ce: "Na'am, na kasance ina yi wa mutanen Makka kiwon dabbobi suna biya na wasu 'yan kuɗaɗe." [Bukhari #2262].

An karɓo daga Miƙdam (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani wanda zai ci abin da ya fi wanda ya nema ta sana'ar hannunsa, kuma lalle Annabin Allah Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kasance yana cin abincin da ya nema ta sana'ar hannunsa." [Bukhari #2072].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da manzanni cewa dukkansu addininsu guda ne, watau kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, kuma Allah ne Ubangijinsu ba su da wani Ubangiji ba shi ba, don haka ya umarce su su kiyaye dokokinsa su aikata abin da ya umarce su da shi su guje wa abin da ya hane su.
Allah kuma ya bayyana cewa duk da wannan haɗin kai da ke tsakanin manzannin Allah da gamuwarsu a kan tushen addini, watau Tauhidi, sai ga shi mabiyansu a bayansu sun rarraba a tsakaninsu a kan lamarin addini, sun zama ƙungiya-ƙungiya, kowace ƙungiya tana alfahari da abin da ta kama a matsayin addinin Allah ba ruwanta da abin da sauran suke kai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya fita harkarsu gaba ɗaya da abin da suke ciki na jahilci da ruɗu har zuwa lokacin da azaba za ta sauka a kansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya soke wani zaton banza da suke yi wa kansu na ganin cewa abin da ya ba su na dukiya da 'ya'ya a rayuwar duniya ya gaggauto musu da wani alheri ne wanda suka cancance shi saboda matsayinsu a wurinsa. Allah ya tabbatar musu da cewa wannan zaton nasu ba gaskiya ba ne, Allah dai yana yi musu abin da yake musu ne a matsayin talala, to amma ba sa jin hakan ko a jikinsu, don haka suke wancan banzan zaton.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah ya raba muku halayyarku kamar yadda ya raba muku arzikinku, kuma lalle Allah yana bayar da duniya ga wanda yake so da wanda ma ba ya so, to amma ba ya bayar da imani sai ga wanda yake so." [*Alhakim* juzu'i na 1, shafi na 348-349 da *Al-Albani, As-Sahiha* # 2714].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mumini shi ne wanda ya haɗa kyautata aiki tare da tsoron Allah.

2. Mumini shi ne wanda yake ayyukan alheri, to amma yana jin tsoron ko ba a karɓa ba.

3. Babu abin da ya dace mutane su yi tsere a kansa kamar ayyukan alheri masu kusantar da bawa ga Ubangijinsa.

4. Duk waɗanda suka siffantu da siffofin da Allah ya ambata a waɗannan ayoyi to babu shakka sun wuce sa'a, babu mai cim musu sai wanda ya yi aiki irin nasu.

Suratul Mu'uminun (57-61)
إِنَّ ٱلَّذِينَ هُم مِّنۡ خَشۡيَةِ رَبِّهِم مُّشۡفِقُونَ ٥٧ وَٱلَّذِينَ هُم بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ يُؤۡمِنُونَ ٥٨ وَٱلَّذِينَ هُم بِرَبِّهِمۡ لَا يُشۡرِكُونَ ٥٩ وَٱلَّذِينَ يُؤۡتُونَ مَآ ءَاتَواْ وَّقُلُوبُهُمۡ وَجِلَةٌ أَنَّهُمۡ إِلَىٰ رَبِّهِمۡ رَٰجِعُونَ ٦٠ أُوْلَٰٓئِكَ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَهُمۡ لَهَا سَٰبِقُونَ ٦١

57. Lalle waɗanda su suke cike da tsoron Ubangijinsu.

58. Kuma waɗanda suke imani da ayoyin Ubangijinsu.

59. Kuma waɗanda ba sa shirka da Ubangijinsu.

60. Kuma waɗanda suke ba da abin da suka bayar (na ayyukan kirki), alhali kuwa zukatansu suna tsorace, don kuwa lalle su masu komawa ne zuwa ga Ubangijinsu.

61. Waɗannan su ne suke gaggawa ga ayyukan alheri, suna kuma masu rige-rige gare su.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffofin bayinsa masu gaggawa wajen ayyukan alheri zaɓaɓbu a wurinsa, da cewa su ne masu siffofi kamar haka:
Na ɗaya, su ne waɗanda suke cike da tsoron Ubangijinsu duk kuwa da cewa sun yi imani da shi sun kuma kyautata ayyukansu.
Na biyu, su ne waɗanda suke yin imani da ayoyin littafin Ubangijinsu yayin da suka ji ana karanta musu su.
Na uku, su ne waɗanda suke kaɗaita Ubangijinsu ba sa shirka da shi; shirka ta bayyane ko ta ɓoye, ƙarama ko babba.
Na huɗu, su ne waɗanda suke matuƙar ƙoƙari wajen aikata alheri suke kusantar Allah da aikata kyawawan ayyuka, to amma suna cike da tsoron ko za a karɓa ko ba za a karɓa ba yayin da suka koma ga Allah ranar alƙiyama.
Sai Allah ya tabbatar da cewa waɗannan da suka siffantu da waɗannan kyawawan siffofi su ne waɗanda suke gaggawa wajen ayyukan alheri, suke rigegeniya a junansu kuma su ne suka yi fintinkau babu mai iya cim musu sai wanda zai yi aiki irin nasu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saboda rahamar Allah ga bayinsa bai ɗora musu abin da ya fi ƙarfinsu ba a cikin duk abubuwan da ya shar'anta musu.

2. Mutumin da gafala ta lulluɓe masa zuciya ba zai iya isa ga shiriyar Alƙur'ani ba.

3. Yawan ni'ima idan ba ta haɗu da shiriyar Allah ba, to jagora ce zuwa ga azabar Allah ranar alƙiyama.

4. An ambaci cewa za a kama mawadatan kafirai da azaba saboda su ne sanadiyyar ɓacewar talakawansu, domin su ne suke hana talakawansu karɓar gaskiya, in ba haka ba da sun yi imani sun bi ta, domin sun fi saukin kai wajen sauraron gaskiya da karɓar ta saboda yawanci ba sa tare da abubuwan da suke hana mutane karɓar gaskiya, kamar tunanin rasa wani shugabanci ko kuɓucewar wata maslaha ta duniya.

5. Al'ada ce ta masu ƙin gaskiya a koyaushe kuma a ko'ina su mayar da gaskiyar da ake faɗa musu da masu faɗa musu gaskiyar ababen izgili da aibantawa da suka.

6. Duk wanda zai yi zuzzurfan tunani game da Alƙur'ani ya yi masa karatun ta-nutsu, to babu shakka zai fahimci cewa daga Allah yake ba maganar wani ɗan'adam ce ba.

7. Duk wanda ya san tarihin Manzon Allah Muhammadu (ﷺ) da tasowarsa da halayensa, to tabbas zai tabbatar da cewa ba maƙaryaci ne ba, Manzo ne zaɓaɓɓe daga Allah.

8. Kafiran Kuraishawa sun san tarihin Manzon Allah sarai da gaskiyarsa da amanarsa da kamewarsa tun yana ƙarami har ya girma Allah ya ba shi manzanci, sai dai kawai sun ƙaryata shi ne don girman kai da hassada da makauniyar biyayya ga magabatansu.

9. Bisa ga sunnar Allah a wannan rayuwa ta duniya yawancin mutane ba sa son gaskiya. Don haka ba a gane gaskiya da yawan mabiyanta ko a gane ƙarya da ƙarancin masu riƙo da ita; ana gane gaskiya ne da ƙarfin hujja da ingancin dalili, duk abin da ya saba mata kuwa to ƙarya ce komai yawan mabiyansa.

10. Tsarin gudanar da halittu duka ya ginu ne a kan gaskiya da adalci; da a ce bisa son zuciya da rashin gaskiya aka gina sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu, da tuni gininsu ya rushe ƙarshensu kuma ya zo. Wannan yana nuna haɗarin bin son zuciya a komai.

11. Kafin zuwan Musulunci Larabawa al'umma ce da ba ta da wani matsayi na a zo a gani a cikin sauran al'ummu. Zuwan Musulunci da saukar Alƙur'ani a cikinsu shi ne ya ɗaukaka darajarsu ya sa suka zama abin alfahari a duniya yayin da suka yi imani da shi suka yi aiki da hukunce-hukuncensa. Hakanan sauran al'ummun Musulmi da suka zo daga baya sun sami ɗaukaka ne ta hanyar Musulunci da Alƙur'ani. Larabawa da al'ummun Musulmi ba su ƙaskanta ba a duniya a yau har sai da suka bijire wa koyarwar Alƙur'ani.

Suratul Mu'uminun (62-71)

وَلَا نُكَلِّفُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَا ۚ وَلَدَيْنَا كِتَٰبٌ يَنطِقُ بِٱلْحَقِّ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿٦٢﴾ بَلْ قُلُوبُهُمْ فِى غَمْرَةٍ مِّنْ هَٰذَا وَلَهُمْ أَعْمَٰلٌ مِّن دُونِ ذَٰلِكَ هُمْ
لَهَا عَٰمِلُونَ ﴿٦٣﴾ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَخَذْنَا مُتْرَفِيهِم بِٱلْعَذَابِ إِذَا هُمْ يَجْـَٔرُونَ ﴿٦٤﴾ لَا تَجْـَٔرُوا۟ ٱلْيَوْمَ ۖ إِنَّكُم مِّنَّا لَا تُنصَرُونَ ﴿٦٥﴾ قَدْ كَانَتْ ءَايَٰتِى تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ
فَكُنتُمْ عَلَىٰٓ أَعْقَٰبِكُمْ تَنكِصُونَ ﴿٦٦﴾ مُسْتَكْبِرِينَ بِهِۦ سَٰمِرًا تَهْجُرُونَ ﴿٦٧﴾ أَفَلَمْ يَدَّبَّرُوا۟ ٱلْقَوْلَ أَمْ جَآءَهُم مَّا لَمْ يَأْتِ ءَابَآءَهُمُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٦٨﴾ أَمْ لَمْ
يَعْرِفُوا۟ رَسُولَهُمْ فَهُمْ لَهُۥ مُنكِرُونَ ﴿٦٩﴾ أَمْ يَقُولُونَ بِهِۦ جِنَّةٌ ۚ بَلْ جَآءَهُم بِٱلْحَقِّ وَأَكْثَرُهُمْ لِلْحَقِّ كَٰرِهُونَ ﴿٧٠﴾ وَلَوِ ٱتَّبَعَ ٱلْحَقُّ أَهْوَآءَهُمْ
لَفَسَدَتِ ٱلسَّمَٰوَٰتُ وَٱلْأَرْضُ وَمَن فِيهِنَّ ۚ بَلْ أَتَيْنَٰهُم بِذِكْرِهِمْ فَهُمْ عَن ذِكْرِهِم مُّعْرِضُونَ ﴿٧١﴾

62. Ba Ma kuwa ɗora wa kowane rai wani abu sai wanda zai iya. Kuma a wurinmu akwai littafi da yake furuci da gaskiya, kuma su ba za a zalunce su ba.

63. A'a, ba haka ba ne, zukatansu dai suna cikin gafala daga wannan (littafi mai furta gaskiya), suna kuma da wasu ayyukan ban da waɗannan waɗanda suke aikatawa.

64. Har yayin da Muka kama mawadatansu da azaba sai ga su suna kururuwa.

65. (Sai a ce da su): “Kada ku yi kururuwa a yau; lalle ku ba za a kare ku ba daga gare Mu.

66. “Haƙiƙa ayoyina sun kasance ana karanta muku su, sai kuka zamanto kuna komawa da baya.

67. “Kuna masu girman kai (na ƙin imani) a wurinsa (Ɗakin Ka’aba), kuna masu hira, kuna ɓata (Alƙur’ani).”

68. Me ya sa ne ba su yi zuzzurfan tunani ba game da Alƙur’ani, ko kuwa wani abu ne ya zo musu da bai zo wa iyayensu na farko ba?

69. Ko kuwa ba su san Manzonsu ba ne, don haka ba su tantance da shi ba?

70. Ko kuwa cewa suke yi ya taɓu? A'a, ya zo musu ne da gaskiya, sai dai yawancinsu masu ƙin gaskiya ne.

71. Da kuma Alƙur’ani ya biye ma son ransu, to da lallai sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu duka sun lalace. A’a, Mun dai zo musu ne da abin alfaharinsu, amma kuma suna masu bijire wa abin alfaharin nasu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ba ya ɗora wa wani mutum wani abu sai abin da zai iya ɗauka. Ya tabbatar da cewa a wajensa akwai wani littafi wanda ya tabbatar wa kowa aikinsa, wannan littafi yana furta gaskiyar da babu wani kokwanto game da ita. Kuma za a yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa, babu wanda za a zalunta a kama shi da laifin da bai yi ba ko a yi masa ƙwauron ladansa.
Sannan kuma Allah ya bayyana cewa zukatan kafirai suna cikin gafala ba sa tuna wannan littafi mai furta gaskiya, hakanan ba sa tuna littafin da aka saukar musu na shari’a, baya ga kafircinsu suna da wasu miyagun ayyukan da suke aikatawa, don haka kada su yi mamakin yadda Allah ya jinkirta azabtar da su; ya yi musu haka ne domin su ci gaba da aikata sauran ayyukansu miyagu har su cancanci mummunar azabar Allah da take jiran su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin azabar da take jiran su a ranar alƙiyama, lokacin da zai kama masu jin daɗinsu na duniya da azabarsa sai kawai a riƙa jin su suna kururuwa suna neman taimako. Sai a nuna musu cewa su fitar da tsammanin samun tsira daga azabar Allah a wannan rana, don haka su ma daina kururuwa da ihu domin ihunsu duk na banza ne babu wanda zai taimaka musu ya kuɓutar da su daga azabar Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa za a tunatar da su laifukansu na duniya waɗanda suka jefa su cikin wannan mawuyacin hali; da cewa a duniya an riƙa karanta musu ayoyin Allah, to amma sai suka riƙa nokewa suna juya baya don ba sa son su saurare su. Suna aikata wancan laifi ne tare da nuna wa mutane girman kai da sunan wai su ne masu Masallaci mai alfarma, alhali ba su ne ba, domin ahalin wannan Masallaci su ne masu tsoron Allah. Hasali ma sukan haɗu da daddare a cikin Ka’aba suna hira suna faɗar miyagun maganganu game da Alƙur’ani da Manzo (ﷺ), don haka masu yin wannan mummunan aiki a jikin Ɗakin Ka’aba ai ba su tsarkake shi ba, ba su kuma ga girmansa yadda ya kamata ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa me ya hana waɗannan mushirikai su tsaya su yi dogon tunani dangane da Alƙur’ani irin wanda zai sanya su su yi imani da shi su yi aiki da karantarwarsa. Ko kuma dai wannan wani abu ne ya zo musu wanda bai zo wa iyayensu na farko ba, shi ya sa suka bijire masa suka ƙaryata shi, don su ci gaba da rayuwa a kan abin da iyayensu suka rayu a kai na kafirci da ɓata? Ko kuma abin da ya hana su yin imani shi ne ba su san Manzonsu Annabi Muhammadu (ﷺ) da aka aiko musu ba, don haka ba su tantance ko yana da gaskiya da amana ko ba ya da su? Haƙiƙa kam sun san komai sarai game da shi, su ne ma suke kiran sa mai gaskiya mai amana.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka.) ya bayyana muguwar maganar da suke faɗa game da Annabi (ﷺ) cewa wai yana da taɓin hankali. Babu shakka wannan ƙarya ce suke faɗa, su ma kuma sun san haka. Sun san ya zo musu ne da gaskiya wadda babu kokwanto a cikinta, to amma yawancinsu ba sa son gaskiya ne domin hassadar da take cikin zuciyarsu da ra'ayin riƙau a kan ɓarnarsu.
Sai Allah ya bayyana cewa da a ce yana gudanar da al'amuransa ne yana tsara su daidai da son zuciyar kafirai, to da sammai da ƙasa duk sun lalace, waɗanda ma suke cikinsu duk sun lalace domin al'amuran za su riƙa wakana ne a bisa jahilci da zalunci, alhali kuma sama da ƙasa ba su tsaya ba sai da adalci da gaskiya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa ya saukar musu da Alƙur'ani wanda ya ƙunshi wa'azi da abin da yake ɗaukaka da alfahari ne a gare su, to amma maimakon su riƙe shi su yi aiki da shi su samu ɗaukaka ta duniya da lahira, sai suka bijire masa suka ƙi imani da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya kauce wa gaskiya to dole ne ya saki hanya a duk al'amuransa.

2. Karyata zuwan ranar alƙiyama da sakamakon da yake cikinta shi ne tushen duk wata ɓarna da wani sharri.

3. Da'awar annabawan Allah ba a gina ta ba a kan cimma wata maslaha ta ƙashin kansu ko tara wani abin duniya. Babbar manufarsu ita ce isar da saƙon Allah, ladansu kuwa yana wurinsa. Haka ne ya wajaba da'awar duk masu da'awa zuwa ga Allah ta zama, wannan kuwa shi ne zai sanya ta samu karɓuwa a zukatan jama'a.

4. Butulce wa ni'imar Allah siffa ce daga cikin siffofin kafirai.

Suratul Mu'uminun (72-77)
أَمۡ تَسۡـَٔلُهُمۡ خَرۡجٗا فَخَرَاجُ رَبِّكَ خَيۡرٞۖ وَهُوَ خَيۡرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ٧٢ وَإِنَّكَ لَتَدۡعُوهُمۡ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٧٣ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ عَنِ ٱلصِّرَٰطِ لَنَٰكِبُونَ ٧٤ *وَلَوۡ رَحِمۡنَٰهُمۡ وَكَشَفۡنَا مَا بِهِم مِّن ضُرّٖ لَّلَجُّواْ فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ٧٥ وَلَقَدۡ أَخَذۡنَٰهُم بِٱلۡعَذَابِ فَمَا ٱسۡتَكَانُواْ لِرَبِّهِمۡ وَمَا يَتَضَرَّعُونَ ٧٦ حَتَّىٰٓ إِذَا فَتَحۡنَا عَلَيۡهِم بَابٗا ذَا عَذَابٖ شَدِيدٍ إِذَا هُمۡ فِيهِ مُبۡلِسُونَ ٧٧

72. Ko kuwa kana neman lada ne a wurinsu, to ladan Ubangijinka shi ya fi alheri; kuma Shi ne Fiyayyen masu arzutawa.

73. Kuma lalle kai tabbas kana kiran su ne zuwa ga hanya madaidaiciya.

74. Lalle kuma waɗanda ba sa yin imani da lahira tabbas su masu bauɗewa ne daga hanya.

75. Da kuwa Mun ji ƙan su Mun kuma yaye musu cutar da take tare da su (ta fari), to tabbas da sun zarce cikin shisshiginsu suna fagamniya.

76. Kuma haƙiƙa Mun kama su da azaba amma ba su miƙa wuya ga Ubangijinsu ba, ba sa kuma ƙaskantar da kai.

77. Har dai yayin da Muka buɗe musu ƙofa mai matsananciyar azaba sai ga su cikinta suna masu yanke ƙauna (daga kowace rahama).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa shin ya nemi wani lada ne a wurin kafirai a kan abin da ya zo musu da shi, wanda haka ya sa suka ƙi yin imani da shi? Babu shakka bai taɓa neman wani lada a wurinsu ba. Don haka Allah ya tabbatar masa cewa ladan da Ubangiji zai ba shi ya fi na waɗannan kafiran, domin shi ne fiyayyen mai arzutawa. To me zai sa shi neman wani abu a wurinsu bayan wanda Allah zai ba shi?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa kyakkyawar shaida ya tabbatar masa cewa lalle shi yana kiran mutane ne zuwa ga tafarki madaidaici wanda babu wata karkata a cikinsa, watau addinin Musulunci. To amma duk da haka kafirai da ba su yi imani da ranar lahira da sakamako ba, suna kauce wa wannan madaidaiciyar hanya ne wadda take kai duk wanda ya bi ta zuwa ga samun rahamar Ubangiji.
Saboda tsananin taurin kan kafirai da dogewarsu a kan kafirci, Allah ya ambaci cewa, da a ce wata cuta ko musiba za ta faɗa musu su roƙi Allah ya yaye musu ita za su yi imani, idan ya yaye musu ita, to tabbas da sun doge a kan shisshiginsu da kafircinsu suna ta ɗimuwa da fagamniya a cikinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya jarrabe su da nau'i iri-iri na musibu, to amma wannan bai sanya su sun ƙaskantar da kansu gaban Allah ba, ba su koma suna bautar da miƙa wuya a gare shi ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Abu Sufyanu ɗan Harbu ya zo wurin Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Ina roƙon ka don Allah don kuma zumunci (watau ya yi musu addu'a Allah ya yaye musu musibar da ta auka musu), domin fa har ta kai yanzu mun shiga cin fatar raƙuma da jini." Sai Allah ya saukar da wannan ayar ta 76. [Nasa'i, *As-Sunanul Kubra* #11289 da Ibn Hibban #967].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kafirai ba za su bar wannan mummunan halin nasu ba har sai lokacin da zai buɗe musu ƙofar wata azaba mai tsanani wadda idan sun tsinci kawunansu a ciki za su ɗebe ƙauna daga samun kowane irin rangwame da mafita. Don haka su guji aikata abin da zai janyo musu irin wannan azabar wadda idan ta zo babu mai mayar da ita in ba Allah ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Da a ce duk ɗan'adam zai yi zuzzurfan tunani game da halittarsa da abin da Allah ya hore masa na gaɓoɓin jikinsa da tsarin ayyuka da ya ɗora su a kai, da wannan kaɗai ya isa ya nuna masa cewa Allah ne kaɗai wanda ya cancanta a bauta masa domin shi kaɗai ne mahalicci ba shi da abokin tarayya.

2. Wajabcin gode wa Allah a kan ɗimbin ni'imominsa da ya yi wa ɗan'adam, ciki har da gaɓoɓin riskar abubuwa yadda suke, watau ji da gani da hankali.

3. Bayanin cewa yawancin mutane ba sa yi wa Allah godiya sai dai su yi masa butulci da aikata kafirci ko saɓo.

4. Da a ce ɗan'adam ya yi zuzzurfan tunani game da sassaɓawar dare da rana, to da lalle ya gane ayoyin Allah da hikimominsa da ke ciki, da kuma hakan ya yi masa jagoranci zuwa ga fahimtar cikar Kudurar Allah da girmansa da cancantar a bauta masa shi kaɗai.

5. Makauniyar biyayya takan hana mutane gane gaskiya duk kuwa da bayyanar hujjojinta a fili.

Suratul Mu’uminun (78-83)

وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَ لَكُمُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَٱلۡأَفۡـِٔدَةَۚ قَلِيلٗا مَّا تَشۡكُرُونَ ٧٨ وَهُوَ ٱلَّذِى ذَرَأَكُمۡ فِى ٱلۡأَرۡضِ وَإِلَيۡهِ تُحۡشَرُونَ ٧٩ وَهُوَ ٱلَّذِى يُحۡىِۦ وَيُمِيتُ وَلَهُ ٱخۡتِلَٰفُ ٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٨٠ بَلۡ قَالُواْ مِثۡلَ مَا قَالَ ٱلۡأَوَّلُونَ ٨١ قَالُوٓاْ أَءِذَا مِتۡنَا وَكُنَّا تُرَابٗا وَعِظَٰمًا أَءِنَّا لَمَبۡعُوثُونَ ٨٢ لَقَدۡ وُعِدۡنَا نَحۡنُ وَءَابَآؤُنَا هَٰذَا مِن قَبۡلُ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٨٣

78. Shi ne kuma (Allah) wanda Ya halitta muku ji da gani da kuma zukata. Kaɗan ƙwarai kuke gode wa (masa).

79. Shi ne kuma wanda Ya halicce ku a bayan ƙasa, kuma zuwa gare Shi za a tattara ku.

80. Kuma Shi ne Yake rayawa Yake kuma kashewa, kuma sassaɓawar dare da rana nasa ne. Me ya sa ba kwa hankalta ne?

81. A’a, sun dai faɗi irin abin da (mutanen) farko suka faɗa ne.

82. (Wato) sun ce: “Yanzu wai idan mun mutu kuma mun zama turɓaya da ƙasusuwa, anya za a kuwa tashe mu?

83. “Haƙiƙa mu da iyayenmu an yi mana alƙawarin wannan tun tuni, wannan ba wani abu ba ne in ban da tatsuniyoyin mutan da.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa masu ƙaryata tashi ranar alƙiyama cewa shi ne wanda ya halitta musu ji domin su amfana da shi a rayuwarsu ta duniya, su saurari duk abin da ya kamata su saurara da shi. Ya kuma halitta musu gani domin su riƙa gani da shi, ya kuma halitta musu zukata domin su fahimci abubuwa da su. To amma duk da haka ba sa yi wa Allah godiya a kan waɗannan ni’imomi da ya yi musu sai `yar kaɗan.
Ya kuma daɗa tabbatar musu da cewa shi ne ya halicci mutane baki ɗaya a bayan ƙasa, kuma gare shi shi kaɗai za a tattara su a ranar alƙiyama don hisabi da sakamako. Kuma shi kaɗai ne yake rayawa yake kashewa kuma babu mai yin haka sai shi. Kuma shi ne kaɗai mai caccanza dare da rana, ya kawo wannan ya tafiyar da wannan, da ya ga dama da sai ya bar dare har abada ko ya bar rana har abada, babu kuma mai iya kawo su sai shi. Don haka ya ja hankalinsu da cewa, yanzu ba za su yi la’akari da wannan Kudurar tasa ba da yadda ya kaɗaita da halitta, su fahimci shi mai iko ne a kan komai har da tayar da su bayan sun mutu?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kafirai masu ƙaryata zuwan alƙiyama, ba su yi aiki da hankalinsu ba sam-sam, kawai sun riƙa faɗar irin maganganun kafirci waɗanda magabatansu na farko suka riƙa faɗa, domin sun riƙa cewa, yanzu su idan sun mutu sun zama ƙasa da rududdugaggun ƙasusuwa shin lalle za a tashe su da ransu don a yi musu hisabi kamar yadda ake faɗa musu? Suka ce ba yanzu aka fara faɗa musu irin waɗannan maganganu ba, a’a, tun lokacin iyayensu su ma an yi musu alƙawari irin wannan kuma har zuwa yau babu abin da ya tabbata, don haka wannan magana tatsuniyar mutanen farko ce kawai babu ƙanshin gaskiya a cikinta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mushirikan Larabawa ba su musunta *Tauhidur Rububiyya* ba, watau sun yarda da ayyukan Allah cewa nasa ne shi kaɗai, kamar halitta da rayawa da kashewa da arzutawa da sauransu. An samu saɓani ne da su wajen tabbatar da Kaɗaitar Allah wajen bauta, watau *Tauhidul Ibada*. Ba su yarda su bauta wa Allah shi

kaɗai ba tare da yi masa shirka ba. Don haka yin imani da *Tauhidur Rububiyya* kaɗai ba zai gamsar ba sai mutum ya yi imani da kaɗaita Allah da bauta, watau *Tauhidul Ibada* ko kuma *Tauhidul Uluhiyya*.

2. Duk wanda ya yi imani da *Tauhidur Rububiyya* to ya lazimce shi ya yi imani da *Tauhidul Uluhiyya*, domin duk wanda yake shi ne mai halitta da kashewa da rayawa da gudanar da rayuwa, to shi ne wanda ya cancanta a bauta masa shi kaɗai.

3. Gudanar da duniya samanta da ƙasanta a kan tsari ɗaya ba tare da samun wata tangarɗa ba dalili ne mai ƙarfi a kan Kaɗaitakar Allah mahalicci.

Suratul Mu'uminun (84-92)
قُل لِّمَنِ ٱلۡأَرۡضُ وَمَن فِيهَآ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٨٤ سَيَقُولُونَ لِلَّهِۚ قُلۡ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ٨٥ قُلۡ مَن رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ ٱلسَّبۡعِ وَرَبُّ ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡعَظِيمِ ٨٦
سَيَقُولُونَ لِلَّهِۚ قُلۡ أَفَلَا تَتَّقُونَ ٨٧ قُلۡ مَنۢ بِيَدِهِۦ مَلَكُوتُ كُلِّ شَيۡءٖ وَهُوَ يُجِيرُ وَلَا يُجَارُ عَلَيۡهِ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٨٨ سَيَقُولُونَ لِلَّهِۚ قُلۡ فَأَنَّىٰ
تُسۡحَرُونَ ٨٩ بَلۡ أَتَيۡنَٰهُم بِٱلۡحَقِّ وَإِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ٩٠ مَا ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ مِن وَلَدٖ وَمَا كَانَ مَعَهُۥ مِنۡ إِلَٰهٍۚ إِذٗا لَّذَهَبَ كُلُّ إِلَٰهِۭ بِمَا خَلَقَ وَلَعَلَا بَعۡضُهُمۡ
عَلَىٰ بَعۡضٖۚ سُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يَصِفُونَ ٩١ عَٰلِمِ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ فَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٩٢

84. Ka ce (da su): "Kasa da abin da yake cikinta na Wane ne, idan kun kasance kun sani?"

85. Ai za ka ji sun ce: "Na Allah ne." Ka ce (da su): "To me ya sa ba kwa wa'azantuwa ne?"

86. Ka ce (da su): "Wane ne Ubangijin sammai bakwai kuma Ubangijin Al'arshi mai girma?"

87. Ai za su ce: "Na Allah ne." Ka ce (da su): "To me ya sa ba kwa taƙawa?"

88. Ka ce (da su): "Wane ne mulkin komai yake a hannunsa, kuma Shi ne Yake kariya, (Shi) kuma ba a kare wani daga gare Shi, idan kun kasance kun sani?"

89. Ai za su ce: "Na Allah ne." Ka ce (da su): "To ta ina ne ake tafiyar muku da hankalinku?"

90. A'a, Mun dai zo musu ne da gaskiya, su kuwa lalle tabbas maƙaryata ne.

91. Allah bai riƙi wani ɗa ba, kuma babu wani abin bauta tare da Shi. (Da ko haka ta faru) to da kowanne abin bauta ya keɓanta da abin da ya halitta, da kuma wani ya yi rinjaye a kan wani. Allah Ya tsarkaka daga abin da suke sifanta (Shi da shi).

92. Shi ne Masanin ɓoye da sarari, to Ya ɗaukaka daga abin da suke shirka (da Shi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya tambayi kafirai masu musunta tashin alƙiyama cewa, ƙasa da halittun da suke kanta na wane ne, in sun sani su faɗa? Allah ya tabbatar da cewa za su amsa su ce na Allah ne shi kaɗai. Sai kuma ya umarce shi da ya ce musu me ya sa ba sa wa'azantuwa tun da sun san da haka, su yarda da cewa Allah yana da ikon ya tashe su da rai bayan sun mutu?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar sa da ya tambaye su wane ne Ubangijin sammai bakwai da Al'arshi mai girma wanda babu wata halitta da ta kai girmansa? Allah ya tabbatar da cewa za su amsa su ce dukkansu mulkin Allah ne shi kaɗai. To sai ya umarce shi da ya faɗa musu cewa, tun da sun san

da haka me ya sa ba za su kiyaye dokokin Allah ba, su bauta masa kamar yadda ya umarce su, kuma su guji aikata abin da ya hana su?
Har wa yau dai ya sake umartar sa da ya tambaye su cewa, wane ne wanda mulkin komai yake a hannunsa shi kaɗai, babu abin da ba ya ƙarkashin ikonsa, shi ne kuma mai taimaka wa wanda ya ga dama daga cikin bayinsa ya kare shi daga duk abin da zai cutar da shi, amma shi babu wani mai iya ba wani kariya daga azabarsa ko ƙaddararsa? Ya kuma umarce su da su faɗa idan sun san akwai wani mai wannan ikon ban da Allah. Sai ya tabbatar da cewa za su amsa masa da cewa mulkin komai yana hannun Allah. To ya faɗa musu cewa, idan haka ne to ta ina ake karkatar musu da hankalinsu har suka yarda su bauta wa wasu gumaka ba Allah ba, ga shi kuma sun yi imani da cewa mulkin komai nasa ne shi kaɗai?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa al'amarin ba kamar yadda suke riyawa ba ne na cewa Allah ba zai iya tashin matattu ba, ya dai zo musu ne da gaskiyar da babu kokwanto a cikinta, kuma su maƙaryata ne kawai, suna yi wa Allah ƙaryar cewa yana da wani abokin tarayya tare da shi ko yana da ɗa ko mata.
Sai ya tabbatar da cewa ba shi da wani ɗa kamar yadda kafirai suke riyawa, kuma babu wani abin bauta na gaskiya tare da shi, da a ce akwai shi kuwa, to da kowane abin bauta ya ƙebanta da kasonsa na abin da ya halitta daga cikin halittu, kuma da kowanne ya nemi ya rinjayi ɗan'uwansa, watau ya fi ƙarfinsa ya ƙwace masa mulkinsa, wanda faruwar haka kuwa za ta jawo lalacewar tsarin gudanar duniya gaba ɗaya. To tun da kuwa hakan bai faru ba, wannan ya nuna abin bauta na gaskiya ɗaya ne shi ne Allah Maɗaukakin Sarki. Ya tsarkaka daga abin da mushirikai suke siffanta shi da shi na cewa yana da ɗa ko wani abokin tarayya.
Allah ya tabbatar da cewa shi ne kaɗai masanin gaibu da abin da yake sarari, babu abin da yake ɓoye gare shi, don haka ya ɗaukaka daga abin da suke yi masa shirka da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yi wa mutumin da ya munana maka kyakkyawar mu'amala. Wannan abu ne mai matuƙar tasiri wajen karkato da zuciyar babban maƙiyi da narkar da gabar da ke cikin zuciyarsa.

2. Wajibi ne bawa ya zamanto mai yawan neman tsarin Allah daga waswasin shaiɗanu da ruɗinsu.

3. Tabbatar da rayuwar Barzahu, watau rayuwar ƙabari bayan mutuwa gabanin tashin alƙiyama.

Suratul Mu'uminun (93-100)
قُل رَّبِّ إِمَّا تُرِيَنِّي مَا يُوعَدُونَ ﴿٩٣﴾ رَبِّ فَلَا تَجۡعَلۡنِي فِي ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٩٤﴾ وَإِنَّا عَلَىٰٓ أَن نُّرِيَكَ مَا نَعِدُهُمۡ لَقَٰدِرُونَ ﴿٩٥﴾ ٱدۡفَعۡ بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُ ٱلسَّيِّئَةَۚ نَحۡنُ أَعۡلَمُ بِمَا يَصِفُونَ ﴿٩٦﴾ وَقُل رَّبِّ أَعُوذُ بِكَ مِنۡ هَمَزَٰتِ ٱلشَّيَٰطِينِ ﴿٩٧﴾ وَأَعُوذُ بِكَ رَبِّ أَن يَحۡضُرُونِ ﴿٩٨﴾ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَ أَحَدَهُمُ ٱلۡمَوۡتُ قَالَ رَبِّ ٱرۡجِعُونِ ﴿٩٩﴾ لَعَلِّيٓ أَعۡمَلُ صَٰلِحٗا فِيمَا تَرَكۡتُۚ كَلَّآۚ إِنَّهَا كَلِمَةٌ هُوَ قَآئِلُهَاۖ وَمِن وَرَآئِهِم بَرۡزَخٌ إِلَىٰ يَوۡمِ يُبۡعَثُونَ ﴿١٠٠﴾

93. Ka ce: "Ubangijina, idan Ka nuna min abin da ake yi musu alƙawari da shi (na azaba).

94. "Ubangijina, kada Ka sanya ni cikin mutane azzalumai."

95. Mu kuma lalle Masu iko ne a kan Mu nuna maka abin da Muke musu alkawari.

96. Ka ingije mummunan abu da wanda ya fi kyau. Mu ne Muka fi sanin abin da suke siffata (ka da shi).

97. Kuma ka ce: "Ubangijina, ina neman tsarinka daga waswasin shaiɗanu.

98. “Ina kuma neman tsarinka Ubangijina kar su zo min.”

99. Har sai idan da mutuwa ta zo wa ɗayansu zai ce: “Ubangijina, Ku mai da ni (duniya) mana.

100. “Don in yi aiki na gari game da abin da na bari (a rayuwata).” Ina! Lalle wannan kalma ce da yake faɗin ta (da bakinsa). A gabansu kuwa akwai shamaki har zuwa ranar tashinsu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ce, idan har Allah ya nuna masa abin da ya yi wa mushirikai alƙawarin aukuwarsa a kansu na azaba to ya roƙe shi da kada ya sanya shi daga cikin azzalumai, watau kada shi ma azabar ta same shi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa yana da ikon ya nuna masa abin da ya yi wa kafirai alƙawarinsa na azaba, kuma babu abin da zai gagare shi.
Sannan ya umarci Annabi (ﷺ) da ya mayar wa da wanda ya munana masa da kyakkyawan sakamako, watau ya yafe masa, ya kuma yi haƙuri a bisa cutarwarsa. Allah ya bayyana masa cewa shi ya fi sanin abin da kafirai suke siffanta Allah da shi na shirka da yadda suke ƙaryata shi, da kuma irin abin da suke siffanta Manzon Allah da shi na ce masa marar hankali ko matsafi ko mawaƙi ko boka.
Allah kuma ya umarce shi ya nemi tsarin Allah daga waswasin shaiɗanu kuma ya tsare shi da kada su halarci kowane irin al’amarinsa.
An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance yana koyar da mu wasu kalmomi da za mu faɗa lokacin firgici, shi ne mu ce: “Ina neman tsari da kalmomin Allah cikakku daga fushinsa da sharrin bayinsa daga kuma waswasin shaiɗanu da kuma kada su halarto ni.” [Abu Dawud #3893 da Tirmizi #3528 da Ahmad #6696].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da mutuwa ta zo ma ɗaya daga cikin mushirikai masu ƙaryata ranar sakamako, ya kuma ga abin da ke shirin faruwa gare shi, to a lokacin ne zai nuna nadamarsa yayin da nadama ba za ta amfane shi da komai ba; zai riƙa roƙon Ubangijinsa Allah cewa ya mayar da shi duniya wai don ya yi aiki na gari idan ya koma. To a nan ne za a tabbatar masa da cewa ya makara, abin da ya nema ba zai samu ba. Kuma wannan maganar yana dai yin ta ne da fatar bakinsa kawai, watau da za a mayar da shi duniya to ba zai cika alƙawarin da ya ɗauka ba na gyara ayyukansa. Sannan Allah ya bayyana cewa waɗanda suka mutu za su ci gaba da zama a cikin shamaki tsakanin rayuwar duniya da ta lahira har lokacin da za a tashe su ya zo, don haka ba za su koma gidan duniya ba don gyara abin da suka ɓata.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan aka sanya mamaci a cikin ƙabarinsa sai wasu mala’iku biyu baƙaƙe masu tsanwayen idanu ana kiran ɗayansu da suna Munkaru, ɗaya kuma Nakiru, sai su ce masa: “Me kake faɗa game da wannan mutumin (watau Annabi Muhammadu (ﷺ)?” Sai ya faɗi abin da ya kasance (a duniya) yana faɗa ya ce: “Shi bawan Allah ne kuma Manzonsa, na shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma Muhammadu bawansa ne kuma Manzonsa.” Sai su ce: “Da man mun san haka kake faɗa.” Sannan sai a faɗaɗa masa ƙabarinsa zira’i saba’in, sannan a haskaka masa shi, sannan a ce masa: “Kwanta ka yi barcinka.” Sai ya ce: “A bar ni in koma zuwa ga iyalina don in ba su labari.” Sai su ce masa: “Ka yi barci kamar barcin angon da babu mai tashin sa sai mafi soyuwar iyalansa gare shi.” Har lokacin da Allah zai tashe shi daga wannan makwancin nasa. Idan kuma munafuki ne sai ya ce: “Na ji mutane suna faɗa, ni ma na faɗi irin abin da suke faɗa. Ban san komai ba.” Sai su ce: “Lalle mun san haka kake faɗa.” Sai a ce wa ƙasa: “Ki haɗe da shi.” Sai ta matse shi sai ƙasusuwan haƙarƙarinsa sun harhaɗe, ba zai gushe ba cikin azaba har zuwa lokacin da Allah zai tashe shi daga wannan makwancin nasa.” [Tirmizi #1071].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Riƙo da nasaba ta wani salihi ko waliyyi ba tare da aikin ƙwarai ba ba zai amfani bawa ba a ranar alƙiyama.

2. Abin la’akari da shi a wurin Allah shi ne, ayyukan mutum kyawawa su rinjayi munana, sai Allah ya yafe wa bawa sauran munanan ayyukansa.

3. Yi wa mutanen kirki izgili wani babban zunubi ne da zai jawo wa mai yin sa mummunar azabar Allah ranar alƙiyama.

Suratul Mu’uminun (101-111)

فَإِذَا نُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَلَآ أَنسَابَ بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَئِذٖ وَلَا يَتَسَآءَلُونَ ١٠١ فَمَن ثَقُلَتۡ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ١٠٢ وَمَنۡ خَفَّتۡ مَوَٰزِينُهُۥ فَأُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ فِي جَهَنَّمَ خَٰلِدُونَ ١٠٣ تَلۡفَحُ وُجُوهَهُمُ ٱلنَّارُ وَهُمۡ فِيهَا كَٰلِحُونَ ١٠٤ أَلَمۡ تَكُنۡ ءَايَٰتِي تُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡ فَكُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ١٠٥ قَالُواْ رَبَّنَا غَلَبَتۡ عَلَيۡنَا شِقۡوَتُنَا وَكُنَّا قَوۡمٗا ضَآلِّينَ ١٠٦ رَبَّنَآ أَخۡرِجۡنَا مِنۡهَا فَإِنۡ عُدۡنَا فَإِنَّا ظَٰلِمُونَ ١٠٧ قَالَ ٱخۡسَـُٔواْ فِيهَا وَلَا تُكَلِّمُونِ ١٠٨ إِنَّهُۥ كَانَ فَرِيقٞ مِّنۡ عِبَادِي يَقُولُونَ رَبَّنَآ ءَامَنَّا فَٱغۡفِرۡ لَنَا وَٱرۡحَمۡنَا وَأَنتَ خَيۡرُ ٱلرَّٰحِمِينَ ١٠٩ فَٱتَّخَذۡتُمُوهُمۡ سِخۡرِيًّا حَتَّىٰٓ أَنسَوۡكُمۡ ذِكۡرِي وَكُنتُم مِّنۡهُمۡ تَضۡحَكُونَ ١١٠ إِنِّي جَزَيۡتُهُمُ ٱلۡيَوۡمَ بِمَا صَبَرُوٓاْ أَنَّهُمۡ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ ١١١

101. Sannan idan aka busa ƙaho to fa babu wata dangantaka (mai amfani) a tsakaninsu a wannan ranar, kuma ba za su tambayi juna ba.

102. To waɗanda ma'aunansu suka yi nauyi waɗannan su ne masu babban rabo.

103. Waɗanda kuwa ma’aunansu suka yi sakayau waɗannan su ne waɗanda suka yi asarar kawunansu, suna masu dawwama a cikin (wutar) Jahannama.

104. (Wutar) tana ƙona fuskokinsu alhali kuwa suna ciccije haƙoransu a cikinta.

105. Yanzu ayoyina ba su zamanto ana karanta muku su ba, sai ya zamana kuna ƙaryata su?

106. Suka ce: “Ya Ubangijinmu, tsiyarmu ce ta rinjaye mu, mun kuma zamo mutane ɓatattu.

107. “Ya Ubangijinmu, Ka fitar da mu daga cikinta, to idan muka sake, to lalle mu azzalumai ne.”

108. Ya ce: “Ku yi min shiru, kada kuwa ku ƙara yi min magana a cikinta.

109. “Lalle yadda lamarin yake, wata ƙungiya daga bayina sun kasance suna cewa: “Ya Ubangijinmu, mun yi imani, sai Ka gafarta mana, kuma Ka ji ƙan mu, Kai ne kuwa Fiyayyen masu jin ƙai.

110. “Sai kuka ɗauke su ababen yi wa izgili, har suka mantar da ku ambatona kuka kuma kasance kuna yi musu dariya.

111. “Lalle Ni Na saka musu a yau saboda haƙurinsu. Lalle kuma su ne marabauta.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu abubuwan na ban tsoro da za su faru a ranar alƙiyama, lokacin da mala’ika Israfilu zai yi busa a ƙaho busa ta biyu yayin da kowa zai fito daga

ƙabarinsa, to a wannan ranar babu wata dangantaka da mutane za su yi wa juna alfahari da ita ko ta amfane su, domin a ranar kowa ta kansa yake, babu kuma tambayar juna game da halin da kowa yake ciki, domin wannan ranar ita ce ranar 'kowa tasa ta fisshe shi'.

An karɓo daga Miswaru ɗan Makhrama (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle duk wata dangantaka ta jini a ranar alƙiyama za ta yanke sai dangantaka da ni da alaƙa da ni da surukutaka da ni.” [Ahmad #18907].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk wanda ma’auninsa na aikin alheri a wannan rana ya yi nauyi, to waɗannan su ne masu samun babban rabo a wurin Allah, domin za su sami abin da suke fata, kuma za a nesanta su daga abin da suke ƙi.
To amma kuma duk wanda ma’aunan ayyukansa suka yi sakayau, watau munanan ayyukansa suka rinjayi kyawawansu, to waɗannan su ne suka yi asarar kawunansu domin sun aikata abin da ya cutar da su sun yi watsi da abin da zai amfane su da sun aikata shi, kamar imani da Allah da ayyukan ƙwarai, to don haka su ne masu shiga wuta su dawwama a cikinta har abada.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin azabar da za a yi musu da cewa wuta za ta riƙa ƙona fuskokinsu, kuma saboda tsananin raɗaɗin azaba da ɓacin rai za su riƙa ciccije haƙoransu. Sai, a cikin zargi, mala’iku su riƙa tambayar su cewa, ashe ba an riƙa karanta musu ayoyin Alƙur’ani a duniya ba, su kuma suka riƙa ƙaryata su? Sai su kuma su furta cewa: “Ya Ubangiji, tsiyarmu ce wadda ka riga ka rubuta mana ta rinjaye mu, kuma mun kasance mutane ɓatattu.”
Sai su ci gaba da roƙon Allah cewa ya fitar da su daga wutar Jahannama suna masu ɗaukar masa alƙawari cewa idan har suka sake komawa cikin kafirci da ɓata, to lalle sun tabbata azzalumai duk abin da ya kama na azaba sai a yi musu.
To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa musu cewa su yi masa shiru kada wani cikinsu ya sake yi masa wata magana.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci irin mummunan aikinsu da ya kai su ga wannan mawuyacin hali, da cewa lalle a duniya wata jama’a daga cikin bayinsa waɗanda suka yi imani da shi sun kasance suna roƙon sa tare da yin kamun ƙafa da imaninsu da shi cewa ya gafarta musu zunubbansu ya ji ƙan su da rahamarsa, domin shi ne Fiyayyen masu rahama.
To amma sai waɗannan kafiran suka mayar da waɗannan muminai abin yi wa izgili, tutur dare da rana ba ƙaƙƙautawa da yi musu ba’a da dariya har hakan ya sa suka manta da ambaton Allah.
Sai Allah ya bayyana musu cewa, to fa shi a yau ya saka wa waɗannan muminai da gidan Aljanna saboda haƙurin da suka yi wajen bin Allah da guje wa saɓa masa, da kuma haƙuri da izgili da cin fuskar da kafirai suke yi musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk tsawon shekarun da bawa zai yi a duniya matuƙar ba a kan biyayyar Allah ya yi su ba, to ɓata lokaci ne kawai da aikin banza yake yi, ranar alƙiyama zai yi nadama wadda ba za ta yi masa amfani ba.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai halicci halittunsa ba sai don wata hikima babba, ita ce su bauta masa shi kaɗai da tabbatar da tsarinsa a bayan ƙasa.

3. Tabbatar da Al’arshin Ubangiji da bayanin girmansa.

4. Duk wanda yake bauta wa wanin Allah to lalle ba shi da wata hujja a kan abin da yake yi.

5. Yi wa Allah yabo da kirari yayin addu’a yana daga cikin ladubban addu’a.

Suratul Mu’uminun (112-118)

قَٰلَ كَمۡ لَبِثۡتُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ عَدَدَ سِنِينَ ١١٢ قَالُواْ لَبِثۡنَا يَوۡمًا أَوۡ بَعۡضَ يَوۡمٖ فَسۡـَٔلِ ٱلۡعَآدِّينَ ١١٣ قَٰلَ إِن لَّبِثۡتُمۡ إِلَّا قَلِيلٗاۖ لَّوۡ أَنَّكُمۡ كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ١١٤
أَفَحَسِبۡتُمۡ أَنَّمَا خَلَقۡنَٰكُمۡ عَبَثٗا وَأَنَّكُمۡ إِلَيۡنَا لَا تُرۡجَعُونَ ١١٥ فَتَعَٰلَى ٱللَّهُ ٱلۡمَلِكُ ٱلۡحَقُّۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ رَبُّ ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡكَرِيمِ ١١٦ وَمَن يَدۡعُ مَعَ
ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ لَا بُرۡهَٰنَ لَهُۥ بِهِۦ فَإِنَّمَا حِسَابُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦٓۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ١١٧ وَقُل رَّبِّ ٱغۡفِرۡ وَٱرۡحَمۡ وَأَنتَ خَيۡرُ ٱلرَّٰحِمِينَ ١١٨

112. Ya ce: “Zaman shekara nawa kuka yi a bayan ƙasa?”

113. Suka ce: “Mun zauna ne yini ɗaya ko rabin yini, sai Ka tambayi (mala’iku) masu lissafin (kwanaki).

114. Ya ce: “Ai ba ku zauna ba sai ɗan lokaci ƙanƙani (dangane da zaman lahira), da a ce kun kasance kun san da haka.”

115. (Allah Ya ce da su): “Ko kuna tsammani ne cewa Mun halicce ku ne ba manufa kuma ku ba za a dawo da ku gare Mu ba?”

116. To Allah Sarki na gaskiya Ya ɗaukaka; babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, (Shi ne) Ubangijin Al’arshi mai girma.

117. Duk wanda ya bauta wa wani abin bauta tare da Allah ba da wata hujja ba game da (wannan bautar), to sakamakonsa wajen Ubangijinsa kawai yake. Lalle su dai kafirai ba za su rabauta ba.

118. Kuma ka ce: “Ya Ubangijina Ka gafarta (mana) kuma Ka ji ƙan mu, Kai ne kuwa Fiyayyen masu jin ƙai.”

To bayan masu laifi sun nemi komawa duniya domin su gyara abin da suka ɓata, sai Allah ya tunatar da su tsawon shekaru da ya ba su a duniya waɗanda za su iya tuba, da sun ga daman haka, to amma ba su yi ba. Ya kuma tambaye su ko shekara nawa suka zauna a bayan ƙasa? Sai suka ba shi amsa da cewa, sun zauna ne yini guda ko ma wani yanki na yini, to amma daga ƙarshe sai suka nemi kawai ya tambayi waɗanda suke kula da lissafin kwanaki da watanni don su faɗa masa haƙiƙanin tsawon lokaci da suka zauna a duniya, domin su a yanzu azabar da suke ciki ta ishe su, ba za su iya tantance haƙiƙanin lissafin ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa zaman da suka yi a duniya ɗan kaɗan ne, idan an kwatanta shi da na lahira marar iyaka, to amma duk da haka ya ishe su su aikata ayyukan alheri da a ce sun sani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa halittunsa gaba ɗaya kashedi da kar su kuskura su yi tsammanin cewa ya halicce su ne don wasa ba tare da wata manufa ba, kuma su daina tunanin cewa ba za su koma gare shi ba don yi musu hisabi da sakamako a kan ayyukansu. Kada ma su kuskura su kawo wannan zaton a zukatansu, domin Allah Sarki na gaskiya ya ɗaukaka a kan yin wani aiki ba tare da manufa ba sai don wasa kawai kuma ya bar bayinsa sasakai ba tare da ya yi musu hisabi a kan ayyuakansu masu kyau da munana ba. Tabbas babu abin bautawa da gaskiya sai shi, shi ne Ubangijin Al’arshi mai girma.
Sai kuma ya gargaɗi wanda yake bauta wa wani tare da Allah ba tare da wata hujja ba, da cewa, mummunan sakamakon aikinsa yana wurin Ubangijinsa, shi ne wanda zai yi masa sakayya ta azaba a kansa, domin kafirai ba za su taɓa rabauta ba har abada.
Sai kuma a ƙarshen Surar Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gafarta masa zunubbansa ya ji ƙan sa da rahamarsa, domin shi ne fiyayyen masu jin ƙai.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya buɗe wannan Sura da cewa: “Wannan Sura ce…” don ya ja hankali a fahimci girman sha’aninta da darajarta.

2. Allah ya bayyana cewa ya saukar da ita tare da cewa duk sauran surorin Alƙur’ani su ma shi ya saukar da su domin kawai ya nuna muhimmancin ita wannan Sura.

3. Muhimmancin gabatar da shimfiɗa yayin bayani a kan wasu al’amura masu girma da muhimmancin gaske.

24-Suratun Nur

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ana kiran ta ne da *'Suratun Nur*' tun zamanin Manzon Allah (ﷺ). Hakanan sunanta yake a cikin bugun Alƙur'ani da littattafan tafsiri da na hadisi. Ba ta da wani suna na biyu.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Duk malamai ra'ayinsu ya haɗu a kan cewa wannan Sura *Madaniyya* ce, watau an saukar da ita ne bayan hijirar Annabi (ﷺ).

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ɗari (100) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *Suratun Nasri* gabanin *Suratul Hajji* a ra'ayin masu ganin *Suratul Hajji Madaniyya* ce.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta a lissafin mutanen Madina da Makka sittin da biyu ne (62), amma a lissafin sauran malamai sittin da huɗu ne (64).

5. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne ƙoƙarin tabbatar da tarbiyya a cikin al'ummar Musulmi ta hanyar kame kai da nisantar duk abubuwan da za su lalata kyakkyawar tarbiyya da zamantakewar al'umma da umarni da duk abubuwan da za su gyara halaye da tsaftace zukata.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Bayanin hukuncin mazinaci da mazinaciya.
• Hukuncin yi wa Musulma kamammiya ƙazafi.
• Hukuncin *li'ani* tsakanin ma'aurata biyu.
• Bayanin wanke Nana A'isha daga tuhumar da munafukai suka yi mata na aikata zina da uƙubar waɗanda suka yi uwa da makarɓiya a cikin batun.
• Tsawatarwa a kan yayata alfasha a cikin muminai maza da mata.
• Umarni da yin afuwa ga wanda ya ɓata maka.
• Hukunce-hukuncen sallama da neman izinin shiga gidaje da ke da mutane a cikinsu da ma marasa mutane a cikinsu.
• Hukunce-hukuncen kame kai da raga kallo na haram.
• Hukuncin sitirar 'ya mace da waɗanda ya halatta ta cire lullubinta a gabansu.
• Zaburarwa game da aurar da marasa aure maza da mata, 'ya'ya da bayi, da bai wa bayi dama su fanshi kawunansu daga bauta.
• Bayanin haramta zaman karuwancin da mata suke yi tun a zamanin jahiliyya.
• Sukan munafukai da nuni zuwa ga mummunan ƙudurinsu ga Annabi (ﷺ).

• Bayar da misalai game da hasken shiriya da ke tare da mumini da duhun da kafiri yake ciki.
• Bayani a kan girman sha'anin wuraren bautar Allah da masu kulawa da su da bautar Allah a cikinsu.
• Kira zuwa ga biyayya ga Annabi (ﷺ) da girmama shi da yi masa ladabi da haɗarin da ke cikin saɓa wa umarninsa da bijire wa koyarwarsa.

Suratun Nur (1)

سُورَةٌ أَنزَلْنَٰهَا وَفَرَضْنَٰهَا وَأَنزَلْنَا فِيهَآ ءَايَٰتٍۭ بَيِّنَٰتٍ لَّعَلَّكُمْ تَذَكَّرُونَ ١

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Wannan Sura ce da Muka saukar da ita Muka kuma wajabta (hukunce-hukuncen da suke cikinta), Muka kuma saukar da ayoyi bayyanannu a cikinta don ku waʾazantu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura ne da bayanin cewa ya saukar da ita, ya kuma wajabta aiki da hukunce-hukuncen da suke cikinta, ya kuma saukar da ayoyi bayyanannu a cikinta domin mutane su waʾazantu da abin da ta ƙunsa na hukunce-hukunce su yi aiki da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An fara da ambaton mazinaciya mace kafin mazinaci namiji, wasu malamai suka ce an yi haka ne saboda wasu dalilai kamar haka:
Na ɗaya, mace ita ce sau tari ummul abaʾisin faruwar zina saboda irin mummunar shiga da take yi a gaban maza da karairaya da ƙanƙanta murya.
Na biyu, zina a wancan lokacin da ayar ta sauka matan su ne aka sani da buɗe ƙofofin zina, domin har kama gidaje suke yi suna zaman kansu, suna kafa tutoci a kai domin a gane sanaʾarsu.
Na uku, laifin zina ya fi zama abin kunya ga 'ya mace fiye da namiji, domin ita ce aka fi zaton kunya tare da ita sannan ita ce danginta suke ƙoƙarin kare mutuncinta, domin ita ce ciki yake bayyana a jikinta.

2. Babu saɓani a tsakanin malamai a kan cewa shuwagabanni su ne ke da ikon zartar da hukunci ga wanda aka same shi da laifin zina, don haka faɗar Allah: "To sai ku yi wa kowanne daga cikinsu bulala ɗari…" da su yake. Maliku da Shafiʾi suna ganin iyayen gida na iya zartar da hukunci a kan bayinsu.

3. Mazinata ba su cancanci rahamar alʾumma ba, domin sun kasance masu rushe ginin alʾumma da tsarkinta.

4. Nuna ba sani ba sabo ga mazinata abu ne da zai taimaka matuƙa wajen kawar da ɓarnarsu ko rage ta.

Suratun Nur (2)

ٱلزَّانِيَةُ وَٱلزَّانِى فَٱجْلِدُوا۟ كُلَّ وَٰحِدٍ مِّنْهُمَا مِاْئَةَ جَلْدَةٍ ۖ وَلَا تَأْخُذْكُم بِهِمَا رَأْفَةٌ فِى دِينِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمْ تُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ ۖ وَلْيَشْهَدْ عَذَابَهُمَا طَآئِفَةٌ مِّنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٢

2. Mazinaciya da mazinaci (idan suka yi zina) sai ku yi wa kowanne ɗaya daga cikinsu bulala ɗari, kada kuwa wani tausayi ya kama ku game da (tabbatar da hukuncin) addinin Allah idan kun kasance kuna imani da Allah da ranar lahira; kuma lalle ne wata ƙungiya daga cikin muminai su halarci (wurin) yi musu haddin.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin wadda ba ta taɓa yin aure ba idan ta yi zina ko namijin da bai taɓa aure ba amma ya yi zina. Allah ya yi umarni da a yi wa kowane daga cikinsu bulala ɗari bayan an tabbatar da laifinsa.
Ana tabbatar da laifin zina ne ta ɗaya daga cikin waɗannan hayoyi guda uku:

1. Samun shaidu huɗu mazaje waɗanda kowannensu ya ga masu laifin dumu-dumu cikin laifinsu, watau kamar turmi da taɓarya.

2. Ikirarin mai laifi.

3. Samuwar ciki ga matar da ba ta da miji ko baiwar da ba ta da maigida, kuma babu wasu alamu na tursasawa ko fyaɗe.
Za a yi wa kowannensu bulala ɗari ta hanyar duka mai raɗaɗi amma ba mai fasa jiki ba.

An karɓo daga Ubadatu ɗan Samit (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku karɓi hukuncin (mazinata) daga gare ni, ku karɓa daga gare ni, Allah ya samar musu mafita; waɗanda ba su taɓa aure ba; mace ko namiji, a yi musu bulala ɗari a kore su (daga garinsu) tsawon shekara ɗaya." [Muslim #1690].

An karɓo daga Abu Huraira da Zaidu ɗan Khalid, Annabi (ﷺ) ya faɗa wa mutumin da ɗansa ya yi zina da wata mata cewa: "Akwai bulala ɗari a kan ɗanka da kuma raba shi da gari tsawon shekara ɗaya." [Bukhari #6827, 6828 da Muslim #1697, 1698].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana muminai su ji wani tausayi yayin zartar da hukuncin haddi a kan waɗannan mazinata biyu har wannan tausayi ya kai ga hana su zartar da hukuncin Allah ko ya sa su su sassauta shi daga yadda Allah ya yi umarni idan har sun yi imani da Allah da ranar lahira.

Haka kuma ya yi umarni da cewa lalle a sami wata ƙungiya daga cikin muminai da za su halarci lokacin da ake zartar da wannan haddi ga waɗancan mazinata don hakan ya zamo darasi gare su har da wasu ma.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin munin zina da bayyana cewa ita ce ta fi saurin zubar da mutuncin mutum.

2. Matar da take aikata zina da namijin da yake aikata zina waɗanda ba su tuba ba, ba ya dacewa mumini kamamme ko mumina kamammiya su aure su.

3. Mazinaci ko mazinaciya in sun tuba sun daina aikata wannan mummunan laifin, ya halatta a aure su, domin tuba tana kankare laifukan da suka gabace ta.n

Suratun Nur (3)

ٱلزَّانِي لَا يَنكِحُ إِلَّا زَانِيَةً أَوْ مُشْرِكَةً وَٱلزَّانِيَةُ لَا يَنكِحُهَآ إِلَّا زَانٍ أَوْ مُشْرِكٌ ۚ وَحُرِّمَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ ۝٣

3. Mazinaci ba ya aure sai da karuwa ko mushirika, karuwa kuma ba ta aure sai da mazinaci ko mushiriki. An kuma haramta wannan ga muminai.

Wannan aya malaman tafsiri sun yi saɓani wajen fassararta:

Wasu suka ce maʾanar ayar ita ce, wanda ya saba da yin zina ba zai so ya auri wata mata ba sai mazinaciya irinsa ko kuma mushirikar da ba ta guje wa zina, tare da cewa haramun ne a gare shi ya aure ta. Hakanan ita ma mace mazinaciya ba za ta yi shaʾawar auren wani ba sai mazinaci irinta ko mushirikin da ba ya guje wa zina tare da haramcin aure tsakaninsu. An kuma haramta wa muminai auren mace mazinaciya ko namiji mazinaci.

An ruwaito wannan fassara daga yawancin magabata, kamar su Abdullahi ɗan Abbas da Abdullahi ɗan Umar da Saʾidu ɗan Musayyab da Saʾidu ɗan Jubair da Mujahid da Ƙatada da Zuhri da sauransu. Wannan shi ne raʾayin Imamu Ahmad da Shaikhul Islam Ibn Taimiyya da sauransu.
Wasu malaman kuma suka ce abin da ayar take nufi shi ne, mazinaci ba ya samun abokiyar zina sai mazinaciya irinsa ko mushirika mai halatta zina, hakanan ita ma mazinaciya ba za ta sami abokin zina ba sai irinta mazinaci ko kuma mushiriki mai halatta zina.
Daga cikin waɗanda suka yi wannan fassara akwai Abdullahi ɗan Abbas (raʾayinsa ne na biyu) da Saʾidu ɗan Jubair (shi ma a wani ƙaulin nasa) da Ikrima da Abdurrahman ɗan Zaid ɗan Aslam. Wannan shi ne zaɓin Ibnu Jarir da Ibnu Kasir da wasunsu.
Akwai wani raʾayin ban da wannan.
A bisa fassarar malamai na farko suna ganin faɗar Allah cewa: "An kuma haramta wannan ga muminai", tana nufin haramun ne mumini kamamme ya auri mazinaciya wadda ba ta tuba ta daina zina ba. Hakanan ita ma mumina kamammiya haramun ne ta auri mazinacin da bai tuba ya daina ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Akwai wani mutum sunansa Marsad ɗan Abu Marsad ya kasance yana taimaka wa waɗanda aka tsare su a Makka su sami kuɓuta ya gudu da su zuwa Madina. To yana da wata dadironsa a Makka tun a lokacin jahiliyya. Wani lokaci sai ya tafi Makka domin kuɓutar da wani Musulmi fursuna a hannun kafirai. Bayan ya shiga Makka sai dare ya yi masa, ya sami ƙarƙashin wata katanga ya zauna cikin inuwar farin wata. Yana nan zaune sai ga dadiron nan tasa, watau Anaƙ, ta nufo inda yake zaune, sai ta kula alamar mutum ne a zaune ƙarƙashin katanga. Da ta ƙara matsawa kusa da shi sai ta gane shi, sai ta ce: "Marsad ne?" Sai ya amsa mata da cewa: "E, Marsad ne." Sai ta yi masa marhabun da lale, ta kuma gayyace shi ya kwana a ɗakinta. Sai ya faɗa mata cewa Allah fa ya haramta zina. Daga jin ya faɗi haka sai kawai ta yi masa kururuwa cewa jamaʾa su fito ga mai ɗauke musu fursunoninsu ya zo. Kafirai da jin haka sai mutum takwas suka bi shi a baya har cikin dutsen *Alkhandama*, ya samu ya shiga wani kogon dutse ya ɓoye. Bayan sun gaji da nemansa ba su gan shi ba, sai suka tafi, shi kuma ya fito ya koma wajen wanda ya yi wa alƙawarin kuɓutar da shi ya kwance masa marinsa ya ɗauke shi suka gudu Madina. Daga baya sai ya je ya sami Manzon Allah ya tambaye shi ko zai iya auren wannan matar Anaƙ? Sai Manzon Allah ya yi shiru bai tanka masa ba har sai da wannan ayar ta sauka, sai Manzon Allah ya ce masa: "Ya kai Marsad, mazinaci ba ya auren wata sai mazinaciya ko mushirika, ita ma mazinaciya ba ta auren wani sai mazinaci ko mushiriki, don haka kada ka aure ta." [Abu dawud #2051 da Tirmizi #3177 da Nasaʾi #3228].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani balagagge mai hankali idan ya jefi wani Musulmi kamamme da aikata laifin zina ko luwaɗi sannan bai kawo shaidu huɗu ba don tabbatar da wannan zargin, to hukuncinsa shi ne bulala tamanin.

2. Babu bambanci tsakanin mace da namiji a wannan hukuncin, ta duka ɓangarorin biyu; mai yin ƙazafi da wanda aka yi wa ƙazafin.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci dangogin uƙuba uku ga mai ƙazafi:
Ta ɗaya, za a yi masa bulala tamanin.

Ta biyu, ba za a karɓi shaidarsa ba har abada.
Ta uku, ya zama fasiƙi matuƙar bai tuba ba.

4. Zina ba ta tabbata sai da hujja, idan babu wata hujja to wannan ƙazafi ne.n

Suratun Nur (4-5)
وَٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ ثُمَّ لَمۡ يَأۡتُواْ بِأَرۡبَعَةِ شُهَدَآءَ فَٱجۡلِدُوهُمۡ ثَمَٰنِينَ جَلۡدَةٗ وَلَا تَقۡبَلُواْ لَهُمۡ شَهَٰدَةً أَبَدٗاۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ۝٤ إِلَّا ٱلَّذِينَ تَابُواْ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ وَأَصۡلَحُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ۝٥

4. Waɗanda kuwa suke jifan mata masu kamun kai sannan ba su kawo shaidu huɗu ba, sai ku yi musu bulala tamanin, kuma kada ku karɓi shaidarsu har abada. Waɗannan kuma su ne fasiƙai.

5. Sai dai waɗanda suka tuba bayan wannan suka kuma kyautata, to haƙiƙa Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin waɗanda za su jefi kamammun mata da aikata laifin zina sannan su kasa kawo shaidu huɗu a kan haka, to sai alƙalai su yi umarni a yi musu bulala tamanin da matsakaiciyar bulala mai raɗaɗi ba mai fasa jiki ba.
Sannan Allah ya bayyana cewa kada masu hukunci su sake karɓar shaidarsu har abada, domin sun rabu da biyayya ga Allah.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku nisanci abubuwa bakwai masu hallakarwa." Sai sahabbai suka ce: "Waɗanne ne ya Manzon Allah?" Sai ya ce: "Shirka da Allah da sihiri da kashe rai da Allah ya haramta kashe shi ba da haƙƙi ba da cin dukiyar maraya da cin riba da tserewa daga fagen daga da jifan mata kamammu gafalallu muminai da zina." [Bukhari #6857 da Muslim #89].

Amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa idan sun tuba daga baya sun kyautata, to Allah mai gafara ne mai jin ƙai, don haka zai gafarta musu abin da ya gabata na laifukan da suka yi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A cikin hukuncin *li'ani* akwai ɗauke ƙunci da damuwa daga wannan al'umma, domin da farko an yi bayanin cewa duk wanda ya jefi wata mata kamammiya da zina to dole ne sai ya kawo shaidu huɗu waɗanda suka gan su dumu-dumu suna aikata zina; idan ya kasa kawo su kuwa to za a yi masa bulala tamanin. To amma idan miji ne da mata al'amarin yana da matuƙar wahala da kuma damuwa, domin lokacin da miji ya tarar da wani tare da matarsa suna zina, idan ya tafi neman shaidu kafin ya dawo wannan mutum ya gama abin da yake ya gudu abinsa. Daga lokacin mijin ya rasa hujjar tabbatar da abin da ya gani. Domin idan ya yi magana to ya yi ƙazafi kenan kuma ya sha bulala tamanin, idan kuma ya yi shiru zai yi ta rayuwa ne cikin baƙin ciki da damuwa. Sai wannan hukunci ya sauka ya kawar da wannan damuwar daga al'umma. Sai aka shar'anta masa ya yi rantsuwa biyar a kan abin da ya ce ya gani a madadin shaidun da ba zai iya kawowa ba. Idan ya yi wannan rantsuwa ya kuɓutar da kansa daga bulala, ya kuma raba kansa da shigo masa da ɗan da ba nasa ba cikin nasabarsa.

2. *Li'ani* ya keɓanci miji ne yayin da ya jefi matarsa da zina, amma ban da mace yayin da ta jefi mijinta da zina.

3. Yana daga cikin falalar Allah da rahamarsa da ya bayyana wa Musulmi munin laifin zina don su ƙara nisantar ta.n

Suratun Nur (6-10)

وَٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ أَزۡوَٰجَهُمۡ وَلَمۡ يَكُن لَّهُمۡ شُهَدَآءُ إِلَّآ أَنفُسُهُمۡ فَشَهَٰدَةُ أَحَدِهِمۡ أَرۡبَعُ شَهَٰدَٰتِۭ بِٱللَّهِ إِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٦ وَٱلۡخَٰمِسَةُ أَنَّ لَعۡنَتَ ٱللَّهِ عَلَيۡهِ إِن كَانَ مِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٧ وَيَدۡرَؤُاْ عَنۡهَا ٱلۡعَذَابَ أَن تَشۡهَدَ أَرۡبَعَ شَهَٰدَٰتِۭ بِٱللَّهِ إِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٨ وَٱلۡخَٰمِسَةَ أَنَّ غَضَبَ ٱللَّهِ عَلَيۡهَآ إِن كَانَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٩ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ وَأَنَّ ٱللَّهَ تَوَّابٌ حَكِيمٌ ١٠

6. Waɗanda kuma suke jifan matayensu (da zina) kuma ba su da wasu shaidu sai su kansu, to shaidar ɗayansu ita ce ya rantsuwa da Allah sau huɗu a kan cewa shi lalle yana daga masu gaskiya.

7. (Rantsuwa) ta biyar kuwa kan cewa tsinuwar Allah ta hau kansa in ya kasance daga cikin maƙaryata.
8. Kuma (abin da) zai kawar mata da azabar haddi shi ne ta yi rantsuwa da Allah sau huɗu kan cewa shi lalle yana daga cikin maƙaryata.

9. (Rantsuwa) ta biyar kuwa kan cewa lalle fushin Allah ya hau kanta idan ya kasance daga masu gaskiya.

10. Ba don falalar Allah gare ku ba da rahamarsa, da kuma cewa Allah Mai karɓar tuba ne, Mai hikima (to da ya kunyata maƙaryaci).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin waɗanda za su jefi matansu na aure da aikata laifin zina sannan ba su da wasu shaidu a kan haka sai su kansu, to hukuncinsu shi ne ya yi rantsuwa huɗu da Allah cewa yana da gaskiya game da laifin da yake zargin matarsa a kai na zina. Sannan a rantsuwarsa ta biyar ya ƙara da yi wa kansa addu'ar la'anar Allah ta tabbata a kansa idan har ƙarya yake yi mata.
Ita ma matar Allah ya bayyana cewa ta cancanci a yi mata haddin zina har sai idan ta yi rantsuwa huɗu da Allah cewa ƙarya mijinta ya yi mata da ya zarge ta da laifin aikata zina, sannan a rantsuwa ta biyar ta ƙara da cewa fushin Allah ya tabbata a gare ta idan har gaskiya ya faɗa. Wannan shi ake kira **li'ani**.

An karɓo daga Sahlu ɗan Sa'ad As-Sa'idi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Uwaimir (Allah ya ƙara masa yarda) ya je wajen shugaban ƙabilarsa Banu Ajlan, watau Asim ɗan Adiyyu ya ce masa: "Me za ku faɗa game da wanda ya sami wani mutum tare da matarsa; shin zai kashe shi ne shi ma a kashe shi ko kuma yaya zai yi? Ka tambaya mini Manzon Allah game da wannan." Sai Asim ya zo wurin Manzon Allah ya yi masa wannan tambayar, to amma sai Manzon Allah ya nuna masa ba ya son irin waɗannan tambayoyin. Da ya koma sai Uwaimir ya tambaye shi ko ya yi masa tambayarsa. Sai ya faɗa masa cewa ya yi wa Manzon Allah wannan tambayar amma ya nuna masa ba ya son irin waɗannan tambayoyi. Sai Uwaimir ya ce shi sai ya yi wa Manzon Allah wannan tambayar. Ya sami Manzon Allah ya ce masa: "Ya Manzon Allah, mutum ne ya sami wani mutum tare da matarsa, shin zai kashe shi ne ku kuma ku kashe shi, ko kuma yaya zai yi?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah ya saukar da ayar Alƙur'ani game da lamarinka kai da matarka." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya umarce su da yin li'ani kamar yadda Allah ya ambata a littafinsa, sai Uwaimir ya yi li'ani da matarsa. Sannan sai ya ce: "Ya Manzon Allah, idan har na zauna da ita to haƙiƙa na zalunce ta." Sai ya sake ta. Sai hakan ya zama hukunci ga ma'auratan da suka yi *li'ani*. [Bukhari #4745 da Muslim #1492].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Hilalu ɗan Umayya ya zargi matarsa da yin zina da Shariku ɗan Sahma'u, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Ka kawo shaida ko a yi maka bulalar

ƙazafi.'' Sai Hilalu ya ce: ''Ya Manzon Allah, idan ɗayanmu ya ga wani mutum a kan matarsa yanzu sai ya bar shi ya tafi neman shaidu?'' Sai Annabi (ﷺ) ya ci gaba da ce masa: ''Ko dai ka kawo shaida ko kuma ka sha bulalar ƙazafi.'' Sai Hilalu ya ce: ''Na rantse da wanda ya aiko ka da gaskiya, lalle ina da gaskiya kuma tabbas sai Allah ya saukar da abin da zai kuɓutar da ni daga haddi.'' Sai Jibrilu ya saukar masa waɗannan ayoyin. Sai Annabi (ﷺ) ya aika aka zo da matar Hilalu, sai Hilalu ya yi rantsuwa, shi kuma Manzon Allah yana cewa: ''Lalle Allah ya san ɗayanku maƙaryaci ne, shin akwai wanda zai tuba daga cikinku?'' Sai ita ma matar ta yi rantsuwa, da ta zo yin rantsuwa ta biyar sai suka dakatar da ita, suka ce mata: ''Wannan lalle ita ce za ta wajabta miki hallaka. Sai ta ɗan yi inda-inda ta ɗan ja da baya har sai da aka yi zaton ko ma za ta fasa rantsuwar ne, sai ta ce: ''Ba zan taɓa kunyata mutanena ba.'' Sai ta ci gaba da rantsuwarta har ta kai ƙarshe....'' [Bukhari #4747].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce Manzon Allah (ﷺ) ya yi hukuncin *li'ani* tsakanin miji da matarsa ya kuma raba tsakaninsu.'' [Bukhari #5314 da Muslim #1494].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutane cewa ba don falalarsa da rahamarsa gare su ba da kuma kasancewarsa mai karɓar tuban bayinsa masu tuba da kuma kasancewarsa mai hikima cikin dukkan lamuransa da shari'arsa, to da ya gaggauto musu da azaba ya kuma kunyata su saboda zunubansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wannan abu da ya faru ga A'isha (Allah ya ƙara masa yarda) a zahirinsa ba alheri ne gare ta ba da sauran muminai, to amma Allah cikin rahamarsa sai ya sanya shi ya zama alheri, domin a sanadiyyarsa A'isha ta sami kyakkyawan yabo daga Allah a cikin saukakkun ayoyin Alƙur'ani da za a yi ta karantawa har lokacin da Allah ya ɗauke wannan Alƙur'anin. Ba ma A'isha kaɗai ba, har sauran matan Annabi (ﷺ) sun sami kyakkyawar shaida daga Allah a sanadiyyar faruwar wannan abu. Baya ga haka, ayoyin da suka sauka dangane da wannan lamari sun ƙunshi bayanai da hukunce-hukunce masu yawa da Musulmi suke buƙatar sanin su duk lokacin da wani abu makamancin wannan ya sake faruwa.

2. Muminai tamkar jiki guda ne, sukan ɗaya daga cikinsu suka ne ga ɗaukacinsu, duk kuma abin da ya faranta wa mutum guda daga cikinsu farin cikinsu ne baki ɗaya. Hakanan duk abin da zai munana wa wani daga cikinsu to su duka ya munana wa. Don haka ya wajaba mumini ya guji sukan ɗan'uwansa mumini domin yin haka daɓa wa cikinsa wuƙa yake yi da kansa.

3. Wajibi ne a kan muminai su riƙa tabbatar da labaran da za a ba su dangane da 'yan'uwansu muminai wanda zai zama suka ga mutuncinsu.

4. Wajibi ne a kan mumini kafin ya furta wata magana ya dubi yanayinta da yanayin wanda maganar ta shafa, ba kowace magana ce ake faɗar ta ba, mutuncin mumini ba ɗaya yake da mutuncin kafiri ba, hakanan mutuncin mutumin kirki ba daidai yake da na banza ba. Laifin cin mutuncin salihin mutum ya fi na cin mutuncin mutumin banza muni nesa ba kusa ba.

5. Mumini kar ya raina aikata laifuka, domin yakan iya raina laifi alhalin babba ne a wurin Allah.

6. Imani na gaskiya yana hana mutum aikata manyan laifuka.n

Suratun Nur (11-18)

إِنَّ ٱلَّذِينَ جَآءُو بِٱلۡإِفۡكِ عُصۡبَةٞ مِّنكُمۡۚ لَا تَحۡسَبُوهُ شَرّٗا لَّكُمۖ بَلۡ هُوَ خَيۡرٞ لَّكُمۡۚ لِكُلِّ ٱمۡرِيٕٖ مِّنۡهُم مَّا ٱكۡتَسَبَ مِنَ ٱلۡإِثۡمِۚ وَٱلَّذِي تَوَلَّىٰ كِبۡرَهُۥ مِنۡهُمۡ لَهُۥ عَذَابٌ عَظِيمٞ ١١ لَّوۡلَآ إِذۡ سَمِعۡتُمُوهُ ظَنَّ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتُ بِأَنفُسِهِمۡ خَيۡرٗا وَقَالُواْ هَٰذَآ إِفۡكٞ مُّبِينٞ ١٢ لَّوۡلَا جَآءُو عَلَيۡهِ بِأَرۡبَعَةِ شُهَدَآءَۚ فَإِذۡ لَمۡ يَأۡتُواْ بِٱلشُّهَدَآءِ فَأُوْلَٰٓئِكَ عِندَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلۡكَٰذِبُونَ ١٣ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ لَمَسَّكُمۡ فِي مَآ أَفَضۡتُمۡ فِيهِ عَذَابٌ عَظِيمٌ ١٤ إِذۡ تَلَقَّوۡنَهُۥ بِأَلۡسِنَتِكُمۡ وَتَقُولُونَ بِأَفۡوَٰهِكُم مَّا لَيۡسَ لَكُم بِهِۦ عِلۡمٞ وَتَحۡسَبُونَهُۥ هَيِّنٗا وَهُوَ عِندَ ٱللَّهِ عَظِيمٞ ١٥ وَلَوۡلَآ إِذۡ سَمِعۡتُمُوهُ قُلۡتُم مَّا يَكُونُ لَنَآ أَن نَّتَكَلَّمَ بِهَٰذَا سُبۡحَٰنَكَ هَٰذَا بُهۡتَٰنٌ عَظِيمٞ ١٦ يَعِظُكُمُ ٱللَّهُ أَن تَعُودُواْ لِمِثۡلِهِۦٓ أَبَدًا إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١٧ وَيُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلۡأٓيَٰتِۚ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ١٨

11. Lalle wadanda suka zo da ƙagaggiyar ƙarya wasu jama'a ne daga cikinku. To kada ku zace shi sharri ne a gare ku; a'a, shi alheri ne a gare ku. Kowanne mutum daga cikinsu yana da sakamakon abin da ya aikata na zunubi. Wanda kuwa ya jiɓinci fara kwaza shi daga cikinsu yana da azaba mai girma.

12. Me ya hana lokacin da kuka ji shi (wato ƙyagen) muminai maza da muminai mata ba su yi wa kawunansu zaton alheri ba suka kuma ce, wannan ai ƙage ne bayyananne?

13. Me ya hana su kawo shaidu huɗu game da shi (ƙagen)? To tun da yake ba su kawo shaidun ba, to wadannan a wurin Allah su ne maƙaryata.

14. Ba don kuwa falalar Allah a gare ku da rahamarsa ba a duniya da lahira, to tabbas da azaba mai girma ta shafe ku game da abin da kuka kutsa cikinsa.

15. Yayin da kuke bayeyeniyarsa (ƙagen) da harsunanku, kuke faɗar abin da ba ku sani ba da bakunanku, kuke kuma tsammaninsa abu ne mai sauƙi, alhali kuwa shi mai girma ne a wurin Allah.

16. Me ya hana yayin da kuka ji shi ku ce: "Bai dace da mu mu yi irin wannan magana ba," (kuma ku ce:) "Subhanallahi! Ai wannan ƙage ne babba!"

17. Allah Yana gargaɗin ku kada ku koma yin irinsa har abada idan kun zamanto muminai.

18. Allah kuma yana bayyana muku ayoyinsa ne, Allah kuwa Masani ne, Mai hikima.

Daga nan har zuwa aya ta 26 Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin wani babban abu ne mai tayar da hankali da ya faru mai dangantaka da ƙazafin zina da munafukai suka yi wa Nana A'isha matar Manzon Allah (ﷺ). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wadannan ayoyi ne don wanke ta daga wannan mummunan zargi maras tushe da gargaɗin muminai game da sakin bakinsu a kan wannan lamari, tare da bayanin mummunan sakamako na wadanda suka jiɓinci ƙirƙiro wannan ƙazafi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa mutanen da suka ƙiri ƙarya da ƙazafi ga Nana A'isha wata jama'a ce daga cikinsu, su ne munafukai. Allah ya tabbatar musu da cewa kada su zaci wannan abu da suka yi na ƙage sharri ne gare su, su muminai, a'a, alheri ne a gare su saboda abin da za su samu daga Allah na lada da kyakkyawan sakamako idan sun yi haƙuri sun fawwala wa Allah komai. Allah ya bayyana musu cewa duk wani wanda yake da hannu a cikin wannan ƙazamin aiki yana da sakamakon zunubinsa, amma wanda ya ɗauki gabaran kwaza wannan labarin to yana da azaba mai girma a wurin Allah.

Malaman hadisi sun ruwaito yadda wannan abin ya faru wanda za mu taƙaita shi kamar haka:
A shekara ta 6 ga hijira Annabi (ﷺ) ya shirya fita don yaƙar ƙabilar Banu Musɗaliƙ, ya fita tare da Nana A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) bayan ya yi wa matansa ƙuri'a, ƙuri'arta ta fito. Bayan Annabi (ﷺ) ya gama abin da ya fita yi, sai shi da rundunarsa suka juyo domin dawowa Madina, sai kuma aka yada zango a kan hanya. Da suka tashi ci gaba da tafiyarsu don su ƙarasa Madina sai aka baro ita A'isha a wurin, domin ta fita daga darbukarta ta zagaya don biyan buƙata irin ta ɗan'adam, sai aka ɗauki darbukar aka ɗora a kan raƙumi ana zaton tana ciki, domin ba ta da nauyi saboda ƙuruciyarta da ƙaramin jikinta a lokacin. To da ta dawo sai ta tarar da Annabi da sahabbai sun tafi sai ta dakata a nan wurin don tana tsammanin idan sun isa gida ba su gan ta ba nan ne za su dawo neman ta. To da akwai masu tsayawa a bayan runduna ga ƙa'ida don duba inda aka yada zango ko an bar wani abu mai muhimmanci su taho da shi. Daga cikin masu irin wannan muhimmin aiki akwai Safwanu ɗan Mu'aɗɗil (Allah ya ƙara masa yarda) , yana zuwa wurin sai ya tarar da A'isha har barci ya ɗauke ta; da ta farka ya kuma gane ita ce sai ya durƙusar da raƙuminsa ya kawar da kansa sai ta hau, bai ce mata uffan ba, ita ma kuma ba ta yi masa wata magana ba. Ya ja akalar raƙuminta har suka cimma Annabi da rundunarsa sun kuma ya da zango domin rurrumi. Da isar Safwan wannan wuri sai munafukai da ke tare da shugabansu Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul nan take sai suka fara zunɗen abin da ya haɗa A'isha da Safwan har aka taho aka bar su a baya, sai Ɗan Salul ya fara cewa lalle wani abu ya faru tsakaninsu na lalata.
Daga nan ne fa labarin ya bazu cikin garin Madina, munafukai suka yi ta yamaɗìɗì da shi, har ma wasu kaɗan daga cikin Musulmai su ma suka riƙa baza labarin.
Wannan abu ya jefa Annabi (ﷺ) da iyalan gidansa da na Sayyadina Abubakar da sauran Musulmi a garin Madina cikin wani mawuyacin hali matuƙa, wanda ta kai har ya daina sakar wa A'isha fuska kamar yadda ya saba yi mata a baya. Ya kuma nemi shawarar wasu daga cikin sahabbansa game da iyalansa waɗanda su kuma suka nuna masa ba su san wani mummunan hali tare da su ba.
Bayan kimanin kwana talatin da aka ɗauka cikin wannan hali, A'isha kuwa tana cikin kuka koyaushe ba dare ba rana a gidan iyayenta bayan ta koma can da izinin Manzo (ﷺ), kuma Manzon Allah bai sami wani wahayi ba daga Allah wanda zai bayyana masa gaskiyar al'amarin. Ana tsaka da haka ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyi ya wanke A'isha tatas daga wannan mummunan zargi, ya tabbatar da tsarkinta da nagartarta. [Bukhari #4750 da Muslim #2770].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Musulmi cewa ai wajaba ya yi lokacin da suka ɗauka ana yaɗa wannan mummunan labarin su yi wa junansu kyakkyawan zato, kada su yarda da zargin ɗan'uwansu mumini ba da hujja ba, su ma fito fili su ƙaryata labarin su ce ƙage ne bayyananne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci masu yi wa Nana A'isha ƙage da cewa, me ya hana su kawo shaidu huɗu don tabbatar da gaskiyar abin da suke zargin ta da aikatawa? To tun da yake ba su kawo waɗannan shaidun huɗu ba, to waɗannan a wurin Allah su ne maƙaryata.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falalarsa da rahamarsa ga muminai wadda ta hana ya gaggauto musu da uƙuba, ya kuma yafe wa wanda ya tuba; ba don haka ba da wata azaba mai girma ta auka musu saboda kutsawa da suka yi cikin wannan lamari na ƙazafi.
Allah ya bayyana irin kutsen da suka yi, watau yayin da suke yayata wannan labari a junansu suna kwaza abin da ba su sani ba da bakunansu suna zaton abu ne mai sauƙi alhalin mai girma ne a wurin Allah, domin abin da ya ƙunsa na danganta wa mumini marar laifi irin wannan babban laifi na zina.
Sannan Allah ya koya wa Musulmi ladabi da tarbiyya game da irin wannan lamari idan nan gaba ya faru sun ji ana yaɗa shi, to su fito fili su nuna rashin dacewar faɗar irin wannan ƙazamar magana, su tsarkake Allah su tabbatar da cewa wannan batu ƙage ne babba.
Allah kuma ya bayyana musu cewa duk waɗannan batutuwa da yake yi musu yana yi musu wa'azi ne don wannan abu da ya faru ya zamanto shi ne na farko shi ne kuma na ƙarshe ba za su ƙara aikata irinsa ba har abada, matuƙar suna matsayinsu na muminai.

Ya tabbatar da cewa yana bayyana musu ayoyinsa ne waɗanda suke ƙunshe da hukunce-hukunce da waʾazozinsa, kuma Allah masanin dukkan ayyukansu ne, babu abin da bai sani ba, zai kuma yi musu sakamako a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin yaɗa ɓarna a cikin muminai ko da kuwa ta hanyar baza labarinta ne, domin yin haka zai taimaka wajen tallata ta a zukatan masu raunin imani.

2. Duk wani mai aikata saɓon Allah da zuci ko da harshe ko da gaɓoɓi, to yana bin hanyar Shaiɗan ne, kuma babu abin da zai jefa shi ciki sai hallaka.

3. Allah ne kaɗai yake kare bayinsa muminai daga aukawa cikin laifuffuka, yake tsarkake su da karɓar tubansu da yafe musu, don haka bawa ya roƙi Allah ya kare shi daga saɓa masa, ya tsarkake shi da karɓar tubansa.

Suratun Nur (19-21)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحِبُّونَ أَن تَشِيعَ ٱلۡفَٰحِشَةُ فِي ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِۚ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ وَأَنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ ١٩ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ وَأَنَّ ٱللَّهَ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ٢٠ ۞يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ وَمَن يَتَّبِعۡ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِ فَإِنَّهُۥ يَأۡمُرُ بِٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِۚ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ مَا زَكَىٰ مِنكُم مِّنۡ أَحَدٍ أَبَدٗا وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يُزَكِّي مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٢١

19. Lalle waɗanda suke son yaɗuwar mummunan abu a cikin waɗanda suka yi imani suna da (sakamakon) azaba mai raɗaɗi a duniya da lahira, kuma Allah (Shi) ne Yake sane, ku ba ba ku san komai ba.

20. Ba don kuwa falalar Allah a gare ku da rahamarsa ba, da kuma cewa lalle Allah Mai tausayi ne, Mai rahama (da kun faɗa cikin hallaka).

21. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku bi hanyoyin Shaiɗan, wanda kuwa duk ya bi hanyoyin Shaiɗan, to lalle shi (Shaiɗan) umarni yake yi da aikata alfasha da abin ƙyama. Ba don kuma falalar Allah a gare ku da rahamarsa ba, da babu ɗaya daga cikinku da zai tsarkaka har abada, sai dai kuma Allah (Shi) Yake tsarkake wanda Ya ga dama, Allah kuwa Mai ji ne, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi masu son ganin munanan laifuka suna yaɗuwa cikin muminai ta hanyar yi musu ƙazafi da yarfe da cewa, lalle suna da azaba mai raɗaɗi a duniya, domin za su haɗu da hukuncin wannan ƙazafi, watau bulala tamanin, a lahira kuma su haɗu da azabar wuta matuƙar sun mutu ba su tuba sun daina wannan mummunan hali ba. Allah ya bayyana cewa yana sane da duk ƙaryar da suke shararawa, kuma shi ne ya san abin da zai zama maslaha ga bayinsa, su ba su san komai a kan hakan ba.

An karɓo daga Sauban (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Kada ku cutar da bayin Allah, kada kuma ku kunyata su, kada ku bibiyi alʾaurarsu, domin duk wanda ya bibiyi alʾaurar ɗanʾuwansa Musulmi, to shi ma Allah zai bibiyi alʾaurarsa har cikin gidansa ya kunyata shi." [Ahmad #22402].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana rahamarsa ga mutane masu laifi, ya nuna musu cewa ba domin falalarsa da rahamarsa gare su ba, to da ya gaggauto musu da azaba tun a nan duniya a kan abin

da suka tafka na ƙarya ga uwar muminai A'isha (Allah ya ƙara masa yarda) , to amma ya jinkirta musu ne domin su tuba ya karɓi tubansu.
Sannan ya kirawo muminai waɗanda suka yi imani suke kuma aiki da shari'arsa ya gargaɗe su a kan su guji bin hanyoyin Shaiɗan wanda yake ƙawata musu ƙarya da ƙage, da cewa duk wanda ya bi hanyoyin Shaiɗan, to lalle zai riƙa umartar sa da munanan ayyuka da miyagun maganganu, ya jefa shi cikin aikata abin da sharia'a ta hana. Ya kuma bayyana wa muminai falalarsa da rahamarsa gare su da har ya zamanto yana karɓar tuban wanda ya yi laifi ya tuba, ba don haka ba da ba zai yafe wa wani mai laifi ba har abada ko da ya tuba. To amma yana karɓar tuban wanda ya ga damar ya yafe masa ya kuma tsarkake shi. Ya tabbatar musu cewa shi mai jin duk maganganunsu ne masanin ayyukansu gaba ɗaya, babu abin da yake ɓuya gare shi, don haka zai yi wa kowa sakamako gwargwadon aikinsa mai kyau da mummuna.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa game da ciyar da makusanta mabuƙata.

2. Hani a kan dakatar da kyautata wa mutum domin shi ya yi rashin kyautatawa.

3. Kwaɗaitarwa a kan yafiya ga masu laifi, da bayyana cewa afuwa da yafiya ga masu laifi musabbabi ne samun gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratun Nur (22)
وَلَا يَأۡتَلِ أُوْلُواْ ٱلۡفَضۡلِ مِنكُمۡ وَٱلسَّعَةِ أَن يُؤۡتُوٓاْ أُوْلِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينَ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۖ وَلۡيَعۡفُواْ وَلۡيَصۡفَحُوٓاْۗ أَلَا تُحِبُّونَ أَن يَغۡفِرَ ٱللَّهُ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٢

22. Kuma kada masu hali da wadata daga cikinku su rantse a kan ƙin ba da (abin hannunsu) ga makusanta da miskinai da masu hijira saboda Allah. Su kuma yi afuwa su yafe. Shin ku ba kwa so ne Allah Ya gafarta muku? Allah kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yin kashedi ne ga mutanen kirki masu wadata da su daina yin rantsuwar ba za su taimaka wa danginsu na kusa da mabuƙata da masu hijira don Allah ba, saboda sun yi musu laifi. Allah ya umarce su da su yafe musu su kuma kau da kai daga laifinsu, ya bayyana musu cewa kamar yadda suke son Allah ya gafarta musu idan sun yi masa laifi sun nemi gafararsa, to su ma su yafe wa waɗanda suka yi musu laifi suka kuma tuba. Allah ya tabbatar musu cewa shi mai gafarta wa bayinsa ne da suka tuba, mai jin ƙan su ne, don haka su ma su yi koyi da shi.
Wannan ayar ta sauka game da Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ne dangane da abin da ya faru tsakaninsa da ɗan innarsa, watau Misɗahu ɗan Usasa (Allah ya ƙara masa yarda) wanda Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya kasance yana tallafa masa yana ciyar da shi, domin shi talaka ne ba shi da ƙarfi. To lokacin da munafukai suka jefi Nana A'isha da ɓatanci sai Misɗahu ya zama daga cikin masu kwaza wannan mummunan labari, sai Sayyadina Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya yi fushi da shi har ya rantse da Allah ba zai ƙara taimaka masa ba domin abin da ya yi wa 'yarsa kuma matar Manzon Allah (ﷺ). To bayan Misɗahu ya tuba an yi masa haddin ƙazafi sai Allah ya saukar da wannan ayar. Yayin da Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ji Allah yana cewa: "Shin ku ba kwa so Allah ya gafarta muku ne?" Sai ya ce: "Wallahi muna son ka gafarta mana ya Ubangijinmu." Sai ya koma ya ci gaba da taimakon Misɗahu, ya kuma yi alƙawarin ba zai daina taimaka masa ba har abada. [Duba, Bukhari #2661 da 2770].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yi wa kamammun mata muminai ƙazafi yana daga cikin miyagun zunubbai.

2. Malamai sun haɗu a kan cewa duk wanda ya zargi A'isha (Allah ya ƙara masa yarda) da zina ya kafirta domin ya ƙaryata ayoyin Alƙur'ani waɗanda suka wanke ta daga zargi. Wasu malamai sun riskar da sauran matan Annabi (ﷺ) da wannan hukunci.

3. Matsayin Annabi (ﷺ) na zamantowa mijin Nana A'isha shi kaɗai ya isa ya wanke ta daga mummunan zargin da munafukai suka yi mata. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai taɓa yi wa wani annabi daga cikin annabawansa zaɓin tumun dare ba, ya haɗa shi da ƙazantacciyar mata mai aikata alfasha, to balle kuma Fiyayyen halittunsa gaba ɗaya zaɓaɓɓensa Annabi Muhammadu (ﷺ), don haka duk matansa tsarkaka ne babu mai aikata laifi irin wannan.

4. Ya dace da mutanen kirki su tsare harsunansu daga miyagun maganganu, su saba wa kawunansu furta magana mai daɗi koyaushe.

5. Duk marar laifin da ake zargi ya kamata ya sanya tsammanin samun mafita daga Allah da kuɓuta daga zargin da ake yi masa.

Suratun Nur (23-26)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ ٱلۡغَٰفِلَٰتِ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ لُعِنُواْ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ٢٣ يَوۡمَ تَشۡهَدُ عَلَيۡهِمۡ أَلۡسِنَتُهُمۡ وَأَيۡدِيهِمۡ وَأَرۡجُلُهُم بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٢٤ يَوۡمَئِذٖ يُوَفِّيهِمُ ٱللَّهُ دِينَهُمُ ٱلۡحَقَّ وَيَعۡلَمُونَ أَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ ٱلۡمُبِينُ ٢٥ ٱلۡخَبِيثَٰتُ لِلۡخَبِيثِينَ وَٱلۡخَبِيثُونَ لِلۡخَبِيثَٰتِۖ وَٱلطَّيِّبَٰتُ لِلطَّيِّبِينَ وَٱلطَّيِّبُونَ لِلطَّيِّبَٰتِۚ أُوْلَٰٓئِكَ مُبَرَّءُونَ مِمَّا يَقُولُونَۖ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٢٦

23. Lalle waɗanda suke jifan kamammun mata waɗanda ba su san me yake faruwa ba, muminai, (suke jifan su da zina), to an la'ance su duniya da lahira, kuma suna da (sakamakon) azaba mai girma.

24. A ranar da harsunansu da hannayensu da kuma ƙafafunsu za su ba da shaida a kansu game da abin da suka kasance suna aikatawa.

25. A wannan ranar Allah zai ba su cikakken sakamakonsu na gaskiya kuma za su san cewa lalle Allah Shi ne gaskiya bayyananniya.

26. Miyagun mata da miyagun maganganu sun dace da miyagun maza. Kuma miyagun maza da miyagun maganganu sun dace ne da miyagun mata. Tsarkakan mata da tsarkakan maganganu sun dace da tsarkakan maza. Kuma tsarkakan maza da tsakakan maganganu sun dace da tsarkakan mata. Su waɗannan (tsarkaka) kuwa wankakakku ne daga abin da suke faɗa (na ƙage a kansu), suna da (sakamakon) gafara da arziki mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lalle masu yin ƙazafi ga kamammun mata muminai waɗanda ba su san abin da ake ciki ba don ɓata musu suna, waɗannan an la'ance su duniya da lahira, bayan abin da yake jiran su na azaba mai girma a lahira. Ranar da harsunansu za su ba da shaida a kansu game da miyagun maganganun da suka yi, hannayensu da ƙafafunsu duk su ba da shaida a kan abin da suka riƙa aikatawa.

Allah ya bayyana cewa a ranar ne za a cika musu sakamakon ayyukansu bisa ga adalci, za kuma su gane cewa Allah shi ne gaskiya, duk kuma abin da zai fito daga wajensa na alheri ko na waninsa, na alƙawari lada ko na narko gaskiya ne, a bayyane yake babu tababa a kansa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku nisanci abubuwa bakwai masu hallakarwa." Sahabbai suka ce: "Waɗanne ne ya Manzon Allah?" Sai ya ce: "Shirka da Allah da sihiri da kashe ran da Allah ya haramta kashewa ba bisa gaskiya ba da cin riba da cin dukiyar maraya da gudowa a ranar yaƙi da yi wa katangaggun mata muminai gafalallu ƙazafi." [Bukhari #2766 da Muslim #89].

An karɓo daga A'isha (Allah ya kara masa yarda.H) ta ce: "An jefe ni da abin da aka jefe ni da shi (na ƙazafi) alhalin ni ban san abin da yake faruwa ba, daga baya labari ya zo min." [*Ibn Jarir*, juzu'i na 18, shafi na 82].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk wani mai ƙazamin hali namiji da mace ko miyagun maganganu da ayyuka suna dacewa ne da miyagun maza da mata irinsu, hakanan duk wani mai tsarki namiji ko mace ko tsarkakakkun maganganu suna dacewa ne da tsarkaka, Allah ya tabbatar da cewa waɗannan tsarkaka wankakku ne daga abin da waɗannan masu miyagun hali suke tuhumar su da shi, kuma suna da wata gafara daga Allah da wani arziƙi na karamci a gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni da aka yi na neman izinin shiga gida daga masu gidan domin kiyaye alfarmar gidaje da mazauna cikinsu ne.
2. Neman izini da sallama yayin shiga gida yana sanya wa masu gidan nutsuwa, yana kuma ɗebe musu kewar mai shigowar, domin shigowarsa kwatsam ba tare da sallama ba zai haifar musu da tsoro da shakka da rashin amincewa.

3. Ba ya halatta ga mutum ya yi fushi yayin da masu gida suka ce masa ya koma kada ya shigo, domin masu gidan ba su hana masa wani haƙƙinsa ba, suna da dama idan sun so su yi masa izini idan ba su so ba su ƙi yi masa.

4. Halaccin shiga wuraren da aka tanada domin ɗaukacin jama'a ba tare da neman izinin kowa ba, kamar wuraren cin abinci da otel-otel da wuraren biyan buƙata da makarantu da wuraren hutawa.

Suratun Nur (27-29)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَدۡخُلُواْ بُيُوتًا غَيۡرَ بُيُوتِكُمۡ حَتَّىٰ تَسۡتَأۡنِسُواْ وَتُسَلِّمُواْ عَلَىٰٓ أَهۡلِهَاۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ٢٧ فَإِن لَّمۡ تَجِدُواْ فِيهَآ أَحَدٗا فَلَا تَدۡخُلُوهَا حَتَّىٰ يُؤۡذَنَ لَكُمۡۖ وَإِن قِيلَ لَكُمُ ٱرۡجِعُواْ فَٱرۡجِعُواْۖ هُوَ أَزۡكَىٰ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ عَلِيمٞ٢٨ لَّيۡسَ عَلَيۡكُمۡ جُنَاحٌ أَن تَدۡخُلُواْ بُيُوتًا غَيۡرَ مَسۡكُونَةٖ فِيهَا مَتَٰعٞ لَّكُمۡۚ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا تُبۡدُونَ وَمَا تَكۡتُمُونَ٢٩

27. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku shiga gidajen da ba naku ba har sai kun nemi izini, kuma kun yi sallama ga masu su. Wannan kuwa shi ya fi alheri a gare ku don ku wa'azantu.

28. To idan ba ku sami kowa a cikinsu ba to kada ku shige su har sai an yi muku izini; idan kuwa aka ce da ku ku koma sai ku koma; wannan shi ya fi tsarki a gare ku. Allah kuwa Masanin abin da kuke aikatawa ne.

29. Babu wani laifi a kanku ku shiga gidaje waɗanda ba wani zaune a cikinsu, kuma akwai kayanku a cikinsu, kuma Allah Yana sane da abin da kuke bayyanawa da abin da kuke ɓoyewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin wasu hukunce-hukunce ne game da sallama da neman izini yayin shiga gidaje. Allah ya kirawo muminai waɗanda suka yi imani da shi suke kuma aiki da shariʾarsa, ya hana su shiga gidajen da ba nasu ba ba tare da sun yi sallama ba sun kuma nemi izinin shiga wajen masu gidan. Ya tabbatar musu da cewa yin hakan shi ne ya fi zama alheri a gare su. Allah ya ba su wannan umarni ne domin su waʾazantu su guji auka wa gidajen da ba nasu ba ba tare da sallama ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya umarce su da cewa idan suka zo gida suka samu ba kowa a gidan, to kada su kuskura su shiga har sai sun sami izini daga wani wanda yake da ikon yi musu izinin shiga. Idan kuwa sun samu da mutane a gidan suka nemi izinin shiga ciki, to amma masu gidan suka nemi su koma kada su shigo musu gida, to su koma su haƙura da shiga wannan gidan, Allah ya tabbatar musu da cewa yin hakan shi ne ya fi musu tsarki a wurin Allah. Allah masanin duk abin da suke aikatawa ne babu abin da yake ɓuya a gare shi, zai kuma yi wa kowa sakayya a kan ayyukansu.

An karɓo daga Abu Saʾid Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wata rana muna zaune a wata majalisa ta mutanen Madina sai ga Abu Musa Al-Ashʾari ya zo hankalinsa a tashe sai ya ce mana: "Na nemi izinin shiga ne wajen Umar (Allah ya ƙara masa yarda) har sau uku amma ba a yi min izini ba, sai na juya na tafi abina. Sai Umar ya fito ya ce mini: "Mene ne ya hana ka shigowa?" Na ce: "Na nemi izini sau uku ba a yi mini ba shi ne na tafi, kuma na ji Annabi (ﷺ) ya ce: "Idan ɗayanku ya nemi izini sau uku ba a yi masa ba to ya koma." Sai Umar ya ce: "Ka kawo hujja a kan wannan maganar ko kuma in doke ka." Shin a cikinku akwai wanda ya ji wannan daga Annabi (ﷺ)? Sai Ubayyu ɗan Kaʾabu ya ce: "Wallahi babu mai tafiya tare da kai sai mafi ƙanƙantar cikinmu." Abu Saʾid ya ce: "To kuma ni ne mafi ƙanƙantarsu, sai na tashi na je na faɗa wa Umar cewa na ji Annabi (ﷺ) yana faɗin haka." [Bukhari #6245 da Muslim #2153].

An karɓo daga Anas ko waninsa ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya je gidan Saʾad ɗan Ubadatu ya nemi izinin shiga ya ce: "Assalamu alaikum wa rahmatullahi." Sai Saʾad ya amsa (a ƙasa-ƙasa) ya ce: "Wa alaikumus salam wa rahmatullahi." Amma Annabi (ﷺ) bai ji shi ba, har sai da ya yi sallama uku, Saʾad ya amsa masa sau uku, amma bai ji shi ba sai ya tafi. Sai Saʾad ya bi shi a baya ya ce: "Ya Manzon Allah, mahaifina da mahaifiyata fansa ne a gare ka, duk sallamar da ka yi a kunnena ka yi ta, kuma na mayar maka amma a ƙasa-ƙasa ba ka ji ni ba ne, ina so ne ka yi mini sallama da yawa don in sami albarka." Sannan ya shigar da shi cikin gidan… [Ahmad #12406].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Busr (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Annabi (ﷺ) ya kasance idan ya zo ƙofar gidan mutane ba ya fuskantar ƙofar da fuskarsa, yakan tsaya ne a gefenta na dama ko na hagu ya ce: "Assalamu alaikum, assalamu alaikum." A lokacin gidaje ba a sa musu labulaye. [Abu Dawud #5186].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin shiga cikin gidajen da ba su keɓanta da wasu ba, watau wuraren da aka tanada don amfanin kowa da kowa, kamar ɗakunan karatu ko shaguna a kasuwanni, ya nuna cewa babu laifi su shiga cikinsu ba tare da neman izini ba. Ya kuma bayyana cewa ya san abin da suke bayyanawa na halayensu da ayyukansu da wanda suke ɓoyewa, zai kuma yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin kawar da idanu daga kallon abin da bai halatta a kalle shi ba ga maza da mata.

2. Kawar da idanu umarni ne na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ɗanʾadam ba zai samu rayuwa mai kyau mai tsada ba sai ya bi umarnin Allah da Manzonsa (ﷺ), idan ya ƙi bin umarninsu kuwa to rayuwarsa za ta lalace duniya da lahira.

3. Allah ya umarci muminai maza da mata da su kawar da idanunsu daga kallon abin da ya haramta ga junansu domin ta haka ne zukatansu za su tsarkaka kuma ba za su ba wa Shaiɗan dama ta ya hallakar da su da takobin shaʾawa ba.

4. Bin wannan umarni na Allah zai haifar wa da muminai haske da nutsuwa a cikin zukatansu. Rashin bin sa kuwa zai gadar musu da duhu da ɗimuwa a cikin zukatansu.

5. Sirrin da ke cikin fara gabatar da kawar da ido a kan kiyaye farji shi ne, shi ido shi ne mai ɗaukar mummunan saƙon shaʾawar aikata zina zuwa zuciya, daga nan kuma sai farji ya gaskata saƙon ko ya ƙaryata shi. Sannan kuma an fi samun jarraba a tare da ido, larurarsa ta fi yawa a cikin jamaʾa, don ba kowa ne yake iya dakatar da shi ba daga kallon abin da bai halatta ba.

6. An halatta wa mai neman auren mace ya kalli wani sashi na jikinta, watau kamar fuskarta da tafukan hannayenta.

Suratun Nur (30-31)

قُل لِّلۡمُؤۡمِنِينَ يَغُضُّواْ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِمۡ وَيَحۡفَظُواْ فُرُوجَهُمۡۚ ذَٰلِكَ أَزۡكَىٰ لَهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا يَصۡنَعُونَ ٣٠ وَقُل لِّلۡمُؤۡمِنَٰتِ يَغۡضُضۡنَ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِنَّ وَيَحۡفَظۡنَ فُرُوجَهُنَّ وَلَا يُبۡدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا مَا ظَهَرَ مِنۡهَاۖ وَلۡيَضۡرِبۡنَ بِخُمُرِهِنَّ عَلَىٰ جُيُوبِهِنَّۖ وَلَا يُبۡدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا لِبُعُولَتِهِنَّ أَوۡ ءَابَآئِهِنَّ أَوۡ ءَابَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوۡ أَبۡنَآئِهِنَّ أَوۡ أَبۡنَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوۡ إِخۡوَٰنِهِنَّ أَوۡ بَنِيٓ إِخۡوَٰنِهِنَّ أَوۡ بَنِيٓ أَخَوَٰتِهِنَّ أَوۡ نِسَآئِهِنَّ أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُنَّ أَوِ ٱلتَّٰبِعِينَ غَيۡرِ أُوْلِي ٱلۡإِرۡبَةِ مِنَ ٱلرِّجَالِ أَوِ ٱلطِّفۡلِ ٱلَّذِينَ لَمۡ يَظۡهَرُواْ عَلَىٰ عَوۡرَٰتِ ٱلنِّسَآءِۖ وَلَا يَضۡرِبۡنَ بِأَرۡجُلِهِنَّ لِيُعۡلَمَ مَا يُخۡفِينَ مِن زِينَتِهِنَّۚ وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٣١قُل لِّلۡمُؤۡمِنِينَ يَغُضُّواْ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِمۡ وَيَحۡفَظُواْ فُرُوجَهُمۡۚ ذَٰلِكَ أَزۡكَىٰ لَهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا يَصۡنَعُونَ ٣٠ وَقُل لِّلۡمُؤۡمِنَٰتِ يَغۡضُضۡنَ مِنۡ أَبۡصَٰرِهِنَّ وَيَحۡفَظۡنَ فُرُوجَهُنَّ وَلَا يُبۡدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا مَا ظَهَرَ مِنۡهَاۖ وَلۡيَضۡرِبۡنَ بِخُمُرِهِنَّ عَلَىٰ جُيُوبِهِنَّۖ وَلَا يُبۡدِينَ زِينَتَهُنَّ إِلَّا لِبُعُولَتِهِنَّ أَوۡ ءَابَآئِهِنَّ أَوۡ ءَابَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوۡ أَبۡنَآئِهِنَّ أَوۡ أَبۡنَآءِ بُعُولَتِهِنَّ أَوۡ إِخۡوَٰنِهِنَّ أَوۡ بَنِيٓ إِخۡوَٰنِهِنَّ أَوۡ بَنِيٓ أَخَوَٰتِهِنَّ أَوۡ نِسَآئِهِنَّ أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُنَّ أَوِ ٱلتَّٰبِعِينَ غَيۡرِ أُوْلِي ٱلۡإِرۡبَةِ مِنَ ٱلرِّجَالِ أَوِ ٱلطِّفۡلِ ٱلَّذِينَ لَمۡ يَظۡهَرُواْ عَلَىٰ عَوۡرَٰتِ ٱلنِّسَآءِۖ وَلَا يَضۡرِبۡنَ بِأَرۡجُلِهِنَّ لِيُعۡلَمَ مَا يُخۡفِينَ مِن زِينَتِهِنَّۚ وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٣١

30. Ka ce da muminai maza su kame idanuwansu kuma su kiyaye farjinsu. Wannan shi ya fi tsarki a gare su. Lalle Allah Masanin abin da suke aikatawa ne.

31. Kuma ka ce da muminai mata su kame idanuwansu kuma su kiyaye farjinsu, kada kuma su fito da adonsu sai dai abin da ya bayyana daga gare shi; kuma su sanya lullubinsu a kan wuyan rigunansu; kada kuma su fitar da adonsu sai ga mazajensu ko iyayensu ko iyayen mazajensu ko ‘ya’yansu ko ‘ya’yayen mazajensu ko ‘yan’uwansu maza ko kuma ‘ya’yan ‘yan’uwansu maza ko ‘ya’yan ‘yan’uwansu mata ko kuma mata ‘yan’uwansu ko kuma bayinsu ko kuma mazaje masu bin su (don neman abinci) ba kuma masu bukatar mata ba, ko kuma ƙananan yara waɗanda ba su san shaʾawar alʾaurar mata ba; kada kuma su buga ƙafafuwansu don a gane abin da suka ɓoye na adon ƙafafunsu (watau mundaye). Kuma ku tuba ga Allah gaba ɗayanku ya ku waɗannan muminai don ku rabauta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa wa maza muminai cewa su kawar da idanuwansu daga kallon matan da bai halatta su kalle su ba, hakanan da kallon alʾaurarsu, su kuma kiyaye farjinsu kada su faɗa cikin aikata haramun kamar zina ko su bayyana tsiraicinsu a fili. Wannan

kame idanuwan nasu shi ne ya fi musu tsarki a wurin Allah, lalle Allah masanin abin da suke aikatawa ne zai kuma yi musu sakayya a kai.Sai kuma ya umarce shi da ya faɗa wa su ma mata muminai da su kawar da idanuwansu daga kallon abin da bai halatta su kalla ba, su kuma tsare farjinsu ta hanyar nesantar zina da suturce shi, kada kuma su kuskura su bayyana adonsu ga mazajen da ba muharramansu ba kuma ba mazajen aurensu ba, sai abin da ya fito wanda ba zai yiwu a ɓoye shi ba kamar tufafi. Sannan ya umarce su da su sanya lullubinsu su rufe wuyan rigunansu domin a daina ganin gashinsu da wuyansu da adonsu na wuya. Kada kuma su bayyana ɓoyayyen adonsu sai ga mazajensu na aure ko iyayensu ko iyayen mazajensu ko ‘ya’yansu ko ‘ya’yan mazajensu ko ‘ya’yan ‘yan’uwansu maza ko ‘ya’yan ‘yan’uwansu mata ko ‘ya’yan ‘yan’uwansu shaƙiƙai ne ko na wajen uba ko na wajen uwa, ko mata ‘yan’uwansu, ko kuma bayin da suka mallaka maza da mata ko kuma maza masu bin su waɗanda sun daina sha’awar mata gaba ɗaya, ko kuma yara waɗanda ba su isa fahimtar al’aurar mata ba saboda ƙankantarsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana mata muminai buga ƙafafunsu a ƙasa don a gane abin da suke ɓoyewa na adonsu, kamar mundaye da makamantansu.Sai kuma ya yi kira ga muminai da su tuba gaba ɗayansu ga Allah saboda kuskuren da za su iya yi na kallon abin da bai halatta ba ko wani laifi na daban, domin su sami babban rabo na gidan Aljanna su kuma kuɓuta daga azabar Allah.

An karɓo daga Buraida (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa Ali: “Ya kai Ali, kada ka bi kallo da wani kallon; na farko ya halatta gare ka amma na biyu bai halatta gare ka ba.” [Abu Dawud #2149].

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ku guji zama a kan hanyoyi.” Sai suka ce: “Ya Manzon Allah, ba mu da zaɓi, wuraren zamanmu ne muna hira.” Sai ya ce: “Idan kun ƙi to ku ba wa hanya haƙƙinta.” Sai suka ce: “Mene ne haƙƙin hanya ya Manzon Allah?” Sai ya ce: “Kawar da idanu da kawar da abin da zai cutar da amsa sallama da umarni da kyakkyawan aiki da hana mummuna. [Bukhari #2465 da Muslim #2121].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni ga iyaye da su aurar da ‘ya’yansu matuƙar sun isa aure, sun kuma sami mazaje na gari da za su aure su.

2. Idan mutum ya mallaki abin yin aure to kada rashin wadatarsa ta hana shi yin aure. Ya yi auren domin Allah ya yi masa alƙawarin wadata shi da abin da zai riƙe iyalansa da shi, don haka ya tsarkake niyya ya dogara ga Allah.

3. Umarni ga waɗanda ba su da halin yin aure da su kame kansu da nesantar duk wani abu da zai jefa su cikin saɓon Allah, ta hanyar kallo ko magana ko shafa da hannu, su ci gaba da neman arziƙi daga Allah, shi zai wadata su daga yalwatacciyar falalarsa.

4. Wanda ya yi aure domin tsare mutuncinsa Allah zai arzuta shi.

5. Allah ya ƙuntata hanyoyin bauta, ya faɗaɗa hanyoyin samun ‘yanci, ya kuma kwaɗaitar a kan ‘yanta bayi.

6. Rabuwa da bauta ta hanyar fansar kai da kuma taimaka wa bawa da dukiya don ya fanshi kansa, wani ƙuduri ne na rage bayi a cikin al’umma, don kada su yi yawa su zama sinadarin yaɗuwar alfasha cikin al’umma.

7. Dukiya kayan Allah ne da ya danƙa ajiyarsa a hannun bawansa, don haka wajibi ne ga bawa da Allah ya ba shi dukiyarsa ya bi umarninsa wajen sarrafa ta a inda ya umarce shi ya kuma yarje masa.

8. Ba a umarci uban gida ya ɗora wa bawansa fansa ba idan ba shi bawan ne da kansa ya nemi hakan ba. Hakanan idan ya san babu wani alheri tare da bawan to ba a umarce shi da ya ɗora masa fansa ba, kamar bawan ya zamo ba shi da hanyar nemo kuɗin fansar kansa sai dai ta hanyar roƙon mutane da matsa musu, ko kuma ya zamanto ba na gari ba wanda idan ya sami ‘yancin kansa ɓarnarsa za ta yawaita cikin al’umma, ko kuma ya bi wata haramtacciyar hanya don nemo kuɗin fansar kansa, kamar hanyar sata ko damfara da makamantansu.

Suratun Nur (32-34)

وَأَنكِحُواْ ٱلۡأَيَـٰمَىٰ مِنكُمۡ وَٱلصَّـٰلِحِينَ مِنۡ عِبَادِكُمۡ وَإِمَآئِكُمۡۚ إِن يَكُونُواْ فُقَرَآءَ يُغۡنِهِمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦۗ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ ٣٢ وَلۡيَسۡتَعۡفِفِ ٱلَّذِينَ لَا يَجِدُونَ نِكَاحًا حَتَّىٰ يُغۡنِيَهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦۗ وَٱلَّذِينَ يَبۡتَغُونَ ٱلۡكِتَـٰبَ مِمَّا مَلَكَتۡ أَيۡمَـٰنُكُمۡ فَكَاتِبُوهُمۡ إِنۡ عَلِمۡتُمۡ فِيهِمۡ خَيۡرٗاۖ وَءَاتُوهُم مِّن مَّالِ ٱللَّهِ ٱلَّذِيٓ ءَاتَىٰكُمۡۚ وَلَا تُكۡرِهُواْ فَتَيَـٰتِكُمۡ عَلَى ٱلۡبِغَآءِ إِنۡ أَرَدۡنَ تَحَصُّنٗا لِّتَبۡتَغُواْ عَرَضَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۚ وَمَن يُكۡرِههُّنَّ فَإِنَّ ٱللَّهَ مِنۢ بَعۡدِ إِكۡرَٰهِهِنَّ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣٣ وَلَقَدۡ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكُمۡ ءَايَـٰتٖ مُّبَيِّنَـٰتٖ وَمَثَلٗا مِّنَ ٱلَّذِينَ خَلَوۡاْ مِن قَبۡلِكُمۡ وَمَوۡعِظَةٗ لِّلۡمُتَّقِينَ ٣٤

32. Kuma ku aurar da marasa aure daga cikinku da kuma na gari daga bayinku da kuyanginku. Idan sun zamanto matalauta to Allah zai wadata su daga falalarsa. Allah kuwa Mai yalwa ne, Masani.

33. Waɗanda kuma ba su sami wadatar yin aure ba su kame kansu har Allah Ya wadata su daga falalarsa. Waɗanda kuwa suke neman fansar kansu daga bayinku, sai ku ba su damar fansar kansu, idan kun san suna da halin iya biya; kuma ku ba su wani abu daga dukiyar Allah da Ya ba ku. Kada kuma ku tilasta wa kuyanginku ‘yan mata a kan yin zina idan sun nemi kame kai, don ku nemi amfanin rayuwar duniya. Wanda duk kuwa ya tilasta su, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai bayan tilastawar da aka yi musu.

34. Haƙiƙa kuma Mun saukar muku da ayoyi mabayyana da kuma izina daga waɗanda suka wuce gabaninku, kuma da gargaɗi ga masu taƙawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su aurar da waɗanda suke ƙarƙashinsu marasa aure maza ko mata idan har sun isa auren kuma suna sha’awar sa, to su hanzarta yi musu shi don kada su faɗa wata mummunar hanya a dalilin rashin auren. Hakanan wanda yake da bayi maza ko mata da suka kai munzalin aure, to su ma su taimaka wajen yi musu auren.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ya ku taron samari, duk wanda yake da halin yin aure daga cikinku, to ya yi aure ya fi taimakawa wajen hana kallon haram, ya fi tsare farji daga faɗa wa zina. Wanda kuwa ba zai iya yin auren ba, to sai ya yi azumi domin shi zai karya masa sha’awa.” [Bukhari #5066 da Muslim #1400].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa yin aure yana daga cikin sabubban samun wadata, don haka kada mutum talaucinsa ya hana shi yin aure, Allah ya yi masa alƙawarin wadata shi idan har ya bi umarninsa ya yi aure domin kare kansa daga faɗawa cikin saɓon Allah. Hakanan kuma kada a hana wani matar aure domin talaucinsa, saboda Allah bai yi umarni da shi ba sai domin shi ne ya ɗauki nauyin arzuta su da ci da sha. Allah mai yalwar arziƙi ne domin idan ya wadatar da wani wannan ba zai rage arziƙinsa da komai ba. Yana sane da halin da bayinsa suke ciki don haka yake umartar su da abin da zai amfane su duniya da lahira.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci wanda bai samu ikon yin aure ba saboda ba shi da abin da zai biya sadaki ko abin da zai riƙe matar da shi, kan ya kame kansa har lokacin da Allah zai wadata shi daga yalwatacciyar falalarsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da suke da bayi masu sha'awar su fanshi kawunansu daga bauta ta hanyar biyan wani kuɗi da za a yanka musu, Allah ya umarci iyayen gidansu da su ba su wannan damar matuƙar sun fahimci za su iya ɗauka kuma sun ga alamar nagarta tare da su. Sannan ya kwaɗaitar da su kan su ba su wani abu daga dukiyar da Allah ya ba su, watau su rage musu wani abu daga cikin dukiyar da suka ɗora musu da farko don fansar kawunansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu kashedi kan tilasta wa kuyangunsu masu son su tsare mutuncinsu a kan yin zina don su nemo musu dukiya.
An tabbatar a cikin ruwayoyi masu dama cewa wannan aya ta sauka ne a kan Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul shugaban munafukan Madina. Shi ne yake tilasta wa kuyanginsa fita don yin zina su sama masa dukiya, to amma su ba sa son haka, suna son tsare mutuncinsu da kame kansu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar domin jan kunnensa da kuma sauran masu irin halinsa da cewa, su ji tsoron Allah su daina. [Dubi, *Ibn Kasir*, juzu'i na 6, shafi na 55-56]. Allah ya bayyana cewa masu irin wannan mummunan aiki suna yi ne don neman abin duniya, ya bayyana cewa wanda duk ya tilasta su har suka aikata wannan laifi ba da son ransu ba, to lalle Allah mai gafara ne ga zunubbansu mai jin ƙai ne gare su, domin ya ɗauke zunubi daga kan wanda aka tursasa shi ya aikata laifi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa ya saukar musu da ayoyi bayyanannu waɗanda suke ɗauke da duk hukunce-hukuncen da suke buƙatar saninsu ba tare da wata rikitarwa ba ko shubuha. Hakanan ya saukar musu da misalai da izinoni daga labaran al'ummun da suka shuɗe na ƙwarai da waɗanda ba na ƙwarai ba, domin su yi koyi da kyawawan ayyukansu su kauce wa munanan ayyukansu. Ya kuma saukar musu wa'azi don masu kiyaye dokokin Allah su wa'azantu da shi, su aikata umarnin Allah su kuma guje wa abin da ya hana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wannan misali da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar yana bayyana cewa a tare da mumini da akwai hasken Allah a cikin zuciyarsa, watau asalin nagartacciyar halittarsa da Allah ya halicce shi da ita *(alfitrah)* kamar wani tacaccen mai ne. Halittarsa a tace take, kuma a shirye take ta karɓi duk wani umarni daga Allah da aiki da shari'arsa. To idan ilimi da imani suka haɗu da wannan asalin halittar sai haske ya kunnu a cikin zuciyarsa kamar yadda wuta take kama lagwanin fitila. Zuciyar mumini garau take babu wani mummunan nufi ko fahimta a cikinta. Idan imani ya ratsa ta sai ta bada wani haske mai ƙarfi saboda yadda ta yi garai-garai kamar ƙarau mai sheƙin lu'ulu'u; sai hasken asalin halitta ya haɗu da hasken imani da na ilimi, ya zama haske a kan haske kenan.

2. Zaitun itaciya ce mai albarka.

3. Shiriya ta Allah ce, shi yake ba da ita ga wanda ya ga dama.

Suratun Nur (35)
۞ٱللَّهُ نُورُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ مَثَلُ نُورِهِۦ كَمِشۡكَوٰةٖ فِيهَا مِصۡبَاحٌۖ ٱلۡمِصۡبَاحُ فِي زُجَاجَةٍۖ ٱلزُّجَاجَةُ كَأَنَّهَا كَوۡكَبٞ دُرِّيّٞ يُوقَدُ مِن شَجَرَةٖ مُّبَٰرَكَةٖ زَيۡتُونَةٖ لَّا شَرۡقِيَّةٖ وَلَا غَرۡبِيَّةٖ يَكَادُ زَيۡتُهَا يُضِيٓءُ وَلَوۡ لَمۡ تَمۡسَسۡهُ نَارٞۚ نُّورٌ عَلَىٰ نُورٖۚ يَهۡدِي ٱللَّهُ لِنُورِهِۦ مَن يَشَآءُۚ وَيَضۡرِبُ ٱللَّهُ ٱلۡأَمۡثَٰلَ لِلنَّاسِۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمُۢ ٣٥

35. Allah ne hasken sammai da ƙasa. Misalin haskensa tamkar alkuki ne da fitila take a cikinsa; fitilar kuma tana cikin ƙarau; ƙaran kuma tamkar tauraro ne na luʾuluʾu, ana kunna ta da man bishiya mai albarka ta zaitun, ita ba daga mahudar rana take ba kuma ba daga mafaɗarta ba, kuma manta kamar zai kama da kansa ko da wuta ba ta taɓa shi ba. Haske kan haske. Allah Yana shiryar da wanda Ya ga dama zuwa ga haskensa. Kuma Allah yana buga misalai ne ga mutane. Allah kuwa Masanin komai ne.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi ne hasken sammai da ƙasa kuma shi ne mai shiryar da waɗanda suke cikinsu, misalin haskensa (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma a zuciyar mumini kamar alkuki ne a jikin bango da fitila take cikinsa; fitilar kuwa tana cikin wani ƙarau mai haske kamar wani tauraro mai haske kai ka ce wani luʾuluʾu ne mai haske. Wannan fitilar ana kunna ta ne daga man wata bishiya mai albarka, ita ce bishiyar zaitun da babu abin da yake kare mata hasken rana safe da yamma. Manta, saboda haskensa da tatuwarsa kamar ya kama wuta da kansa ko da wata wuta ba ta shafe shi ba, to balle kuma ta shafe shi. Hasken wannan fitila a kan hasken wannan ƙaran. To haka hasken zuciyar mumini yake idan hasken shiriya ya haskaka ta. Allah kuma ya tabbatar da cewa yana datar da wanda ya ga dama daga cikin bayinsa ya bi Alƙurʾani, yana kuma bayanin abubuwa daban-daban ga mutane ta hanyar ba su misalai, kuma shi masanin komai ne babu abin da yake ɓoye masa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance idan ya tashi tsayuwar dare yana cewa: "Ya Allah, yabo da godiya da kirari sun tabbata gare ka kai kaɗai, kai ne tsayayye da Zatinka ga sammai da ƙasa da waɗanda suke cikinsu; kuma yabo da godiya da kirari sun tabbata a gare ka kai kaɗai, kai ne hasken sammai da ƙasa da waɗanda suke cikinsu…" [Bukhari #1120 da Muslim #769].

An karɓo daga Abu Musa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya tsaya a cikinmu ya faɗi kalmomi biyar ya ce: "Lalle Allah ba ya barci kuma bai dace shi ya yi barci ba; yana yin ƙasa da maʾaunin adalci yana kuma yin sama da shi, ana kai masa can sama aikin dare kafin na rana da aikin rana kafin na dare. Hijabinsa haske ne, da zai kwaranye shi da lalle hasken fuskarsa ya ƙona duk abin da ganinsa ya kai gare shi na daga halittarsa." [Muslim #179].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin falalar masallaci da gina shi.

2. Umarni da kula da masallatai da share su da tsaftace su da sanya musu turare da samar musu da duk wani abu da za su buƙata don tsare musu matsayinsu.3. Yabon masu kula da addininsu a kowane hali suke ciki, ba sa yarda neman duniya ya shagaltar da su ya mantar da su tsayuwa da haƙƙoƙin Allah da waɗanda ya farlanta a dukiyarsu.

4. Yalwar falalar Ubangiji ga bayinsa, don haka yake yi musu sakayya da mafificin abin da suka aikata har ma da ƙari daga cikin falalarsa.n

Suratun Nur (36-38)

فِي بُيُوتٍ أَذِنَ ٱللَّهُ أَن تُرۡفَعَ وَيُذۡكَرَ فِيهَا ٱسۡمُهُۥ يُسَبِّحُ لَهُۥ فِيهَا بِٱلۡغُدُوِّ وَٱلۡأٓصَالِ ٣٦ رِجَالٞ لَّا تُلۡهِيهِمۡ تِجَٰرَةٞ وَلَا بَيۡعٌ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَإِقَامِ ٱلصَّلَوٰةِ وَإِيتَآءِ ٱلزَّكَوٰةِ يَخَافُونَ يَوۡمٗا تَتَقَلَّبُ فِيهِ ٱلۡقُلُوبُ وَٱلۡأَبۡصَٰرُ ٣٧ لِيَجۡزِيَهُمُ ٱللَّهُ أَحۡسَنَ مَا عَمِلُواْ وَيَزِيدَهُم مِّن فَضۡلِهِۦۗ وَٱللَّهُ يَرۡزُقُ مَن يَشَآءُ بِغَيۡرِ حِسَابٖ ٣٨

36. (Hasken) yana cikin wasu ɗakuna (watau masallatai) waɗanda Allah Ya yi umarni a ɗaukaka, a kuma ambaci sunansa a cikinsu. (Wasu mazaje) suna tasbihi gare Shi a cikinsu safe da yamma.

37. Wasu mazaje ne waɗanda kasuwanci da saye da sayarwa ba ya shagaltar da su daga ambaton Allah da kuma tsai da salla da ba da zakka, suna jin tsoron ranar da zukata da idanuwa suke raurawa.

38. (Suna haka ne) don Allah Ya saka musu da mafi kyan abin da suka aikata, kuma Ya ƙara musu daga falalarsa. Allah kuwa Yana arzuta wanda Ya ga dama ba da iyaka ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wancan haske da ya yi bayaninsa ana samun sa a cikin ɗakunan Allah, watau masallatai waɗanda ya yi umarni a ɗaukaka darajarsu da gine-ginensu, a kuma ambaci sunansa a cikinsu ta hanyar kiran salla da tsai da salla da zikiri. Wasu mazaje suna salla a cikinsu, suna tsarkake Allah domin neman yardarsa safe da yamma. Waɗannan mazaje ne waɗanda harkokin kasuwancinsu da saye da sayarwarsu ba sa shagaltar da su daga ambaton Allah da yin salla yadda ya kamata da bayar da zakka ga masu ita; suna jin tsoron ranar lahira, ranar da zukata suke kaɗuwa suna fatan samun kuɓuta daga azabar Allah, suna kuma jin tsoron ta auka musu. Hakanan idanuwansu suna kaɗuwa domin ba su san ina za su nufa ba don samun tsira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa sun yi haka ne ba don komai ba sai don Allah ya saka musu da mafi kyan ayyukansu, ya kuma ƙara musu daga falalarsa, Allah kuwa yana arzuta wanda ya ga dama ya ba shi sakamako mai ɗimbin yawa ba tare da lissafi ba.

An karɓo daga Usman ɗan Affan (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda ya gina masallaci domin Allah, to Allah zai gina masa kwatankwacinsa a Aljanna." [Bukhari #450 da Muslim #533].

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Annabi (ﷺ) ya yi umarnin a gina masallatai a unguwanni, kuma a tsaftace su a sa musu turare." [Ahmad #26386 da Abu Dawud #455 da Tirmizi #594 da Ibn Majah #759].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ba ya karɓar kyawawan ayyukan kafiri har sai ya yi imani.

2. Misali na farko na kafirai ne waɗanda suka sha wahala tuƙuru wajen gudanar da wasu ayyuka na gari kamar ciyarwa da aikin agaji da tausayi, to sai an zo lokacin da suka fi tsananin buƙatar amfanuwa da waɗannan ayyuka da suka yi sai kawai su neme su sama da ƙasa su rasa su, tamkar wanda yake cikin matsananciyar jin ƙishirwa sai ya hango kawalwalniya daga nesa a wani kwari sai ya nufe shi gadan-gadan, bayan ya wahala ya isa wurinsa sai kawai ya ga babu komai. To kamar haka ne kafiri zai rasa amfanuwa da ayyukansa ranar alƙiyama inda zai haɗu da Ubangijinsa ya cika masa sakamakon shirka da ya yi a duniya.

3. Misali na biyu kuwa na kafirai ne waɗanda suke fagamniya a cikin duffai, babu wani tunani na kirki tare da su, mashigarsu duhu ne hakanan mafitarsu ma duhu ne, maganganunsu da ayyukansu da tunaninsu duka duhu ne a kan duhu, jahilci ne bisa jahilci. Wannan misali ne na kafirai 'yan a bi yarima a sha kiɗa, ba abin da yake gabansu sai bin son zukatansu da na shugabanninsu masu yi musu jagoranci cikin ɓata da saɓon Allah.n

Suratun Nur (39-40)

وَٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَعۡمَٰلُهُمۡ كَسَرَابِۭ بِقِيعَةٖ يَحۡسَبُهُ ٱلظَّمۡـَٔانُ مَآءً حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَهُۥ لَمۡ يَجِدۡهُ شَيۡـٔٗا وَوَجَدَ ٱللَّهَ عِندَهُۥ فَوَفَّىٰهُ حِسَابَهُۥۗ وَٱللَّهُ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ٣٩ أَوۡ كَظُلُمَٰتٖ فِي بَحۡرٖ لُّجِّيّٖ يَغۡشَىٰهُ مَوۡجٞ مِّن فَوۡقِهِۦ مَوۡجٞ مِّن فَوۡقِهِۦ سَحَابٞۚ ظُلُمَٰتُۢ بَعۡضُهَا فَوۡقَ بَعۡضٍ إِذَآ أَخۡرَجَ يَدَهُۥ لَمۡ يَكَدۡ يَرَىٰهَاۗ وَمَن لَّمۡ يَجۡعَلِ ٱللَّهُ لَهُۥ نُورٗا فَمَا لَهُۥ مِن نُّورٍ ٤٠

39. Waɗanda kuwa suka kafirta ayyukansu kamar kawalwalniya ne a wani faƙo wanda mai jin tsananin ƙishirwa yake zaton ruwa ne, har lokacin da ya zo gare ta ba zai samu komai ba sai ya sami Allah a wurinsa, sai Ya cika masa hisabinsa. Allah kuwa Mai saurin hisabi ne.

40. Ko kuma kamar duffai a cikin kogi mai zurfi da raƙumin ruwa ya lulluɓe shi, daga samansa kuma akwai wani raƙumin ruwan, daga samansa (kuma) akwai wani hadari. Duffai wasu a kan wasu; idan ya fito da hannunsa ba zai iya ganin sa ba. Wanda kuma Allah bai sanya wa haske ba, to ba shi da wani haske.

Bayan Allah ya ambaci halin muminai na kasancewa cikin hasken Allah a duniya wanda da shi ne suke riƙo da kyawawan ayyuka, a lahira kuma su sami babban rabo, sai kuma a nan ya ambaci halayen kafirai da asarar da suka tafka a nan duniya da yadda suka kasance cikin duhu yana dukan duhu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk ayyukan da kafirai suka yi masu kyau a nan duniya ba su da wani lada a kansu ranar alƙiyama, domin za su zama kamar kawalwalniya ne a wata ƙasa mai faƙo wanda mai jin ƙishirwa zai hango ya yi zaton ruwa ne, sai ya kama hanya ya nufi inda yake har sai ya je gare shi sai ya ga babu komai, a nan zai yi ta nadama ya kuma ci gaba da jin ƙishirwa. To kamar haka aikin kafiri yake yana zaton zai amfane shi har sai lokacin da ya mutu aka tashe shi sai ya rasa ladan wannan aiki da ya yi, sai ya haɗu da Ubangijinsa a gabansa, shi kuma ya cika masa hisabin aikinsa ba tare da ya tauye komai ba. Allah mai gaggawar hisabi ne, don haka kafirai su daina ganin nisan zuwan wannan rana, tana tafe ba makawa. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar da misali na biyu na halin da kafirai suke ciki, da cewa ayyukansu kamar duffai ne a cikin wani kogi mai zurfi da raƙumin ruwa ya lulluɓe shi daga samansa, a saman wannan raƙumin ruwan akwai wani ma irinsa, sama kuma girgije ya rufe taurarin da yake gane hanya da su, duffai wani kan wani. To duk wanda yake cikin waɗannan duffai idan ya fito da hannunsa ba zai iya ganin sa ba saboda tsananin duhu. To hakanan kafiri yake a nan duniya, yana cikin duhun jahilci da kafirci da shakka da ɗimuwa da toshewar zuciya. Allah ya tabbatar da cewa duk wanda bai arzuta shi da shiriya ba ya ɗora shi a kan aiki da littafinsa, to ba shi da wata shiriya da zai shiryu da ita ko wani littafi da zai haskaka da shi.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah ba ya zaluntar mumini bisa wani kyakkyawan aiki ɗaya, zai yi masa sakayya a kansa a nan duniya, ya kuma saka masa a lahira a kansa. Amma kafiri idan ya aikata kyawawan ayyuka a nan duniya, Allah zai ciyar da shi saboda waɗannan ayyukan, har sai ya je lahira ba zai samu wani aikin lada da za a saka masa a kansa ba." [Muslim #2808].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wata halitta da Allah ya yi a sama ko a ƙasa tana yin tasbihi ga Allah irin tasbihin da ya dace da ita.

2. Allah ne kaɗai mai mulkin sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu, shi ne mai gudanar da komai a cikinsu yadda ya ga dama, don haka bai dace a bauta wa wani ba shi ba.

3. Makoma ta ƙarshe ɗaya ce tak, kowa can ya nufa, ita ce ranar alƙiyama.

Suratun Nur (41-42)

أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يُسَبِّحُ لَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَٱلطَّيۡرُ صَٰٓفَّٰتٖۖ كُلّٞ قَدۡ عَلِمَ صَلَاتَهُۥ وَتَسۡبِيحَهُۥۗ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِمَا يَفۡعَلُونَ ٤١ وَلِلَّهِ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ وَإِلَى ٱللَّهِ ٱلۡمَصِيرُ ٤٢

41. Ba ka gani cewa Allah duk abin da yake sammai da ƙasa yana tasbihi ne gare Shi, haka tsuntsaye kuma sun buɗe fukafukansu sun yi sahu, kowanne ɗayansu ya san sallarsa da tasbihinsa? Allah kuwa Masanin abin da suke aikatawa ne.

42. Kuma mulkin sammai da ƙasa na Allah ne; makoma kuma zuwa ga Allah take.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana nuna wa bayinsa girman ikonsa da kamalarsa, da cewa duk waɗanda suke cikin sammai da waɗanda suke bayan ƙasa suna tsarkake shi. Haka tsuntsaye suna tasbihi da tsarkake shi suna masu buɗe fukafukansu cikin sahu a sararin samaniya. Duk kuwa waɗannan halittun Allah ya san sallar mai yin salla daga cikinsu kamar ɗan'adam da tasbihin mai yin tasbihi daga cikinsu kamar tsuntsaye, kuma Allah masanin abin da suke aikatawa ne, babu wani aiki nasu da bai sani ba.
Sannan ya bayyana cewa Allah ne kaɗai ke da mulkin sammai da ƙasa, kuma kowa zuwa gare shi zai koma ranar alƙiyama domin yi masa hisabi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan matakai na haɗuwar girgije da saukar ruwan cikinsa aikin Allah ne da cikakken ikonsa.

2. Kamar yadda Allah yake ni'imta waɗanda ya ga dama cikin bayinsa da saukar ruwan sama da ƙanƙara, hakanan idan ya ga dama zai iya saukar da azabarsa ta hanyarsu, to amma mutane da dama ba sa tunanin haka don saboda yawan faruwarsa da saukar ƙanƙara ba tare da an cutu ba.

3. Babu mai ɗaukar darasi da izina daga abin da yake gani yau da gobe na canzawar yanayi daga dare zuwa rana ko daga haske zuwa duhu sai mutane masu basira masu zurfin tunani.

Suratun Nur (43-44)

أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يُزۡجِي سَحَابٗا ثُمَّ يُؤَلِّفُ بَيۡنَهُۥ ثُمَّ يَجۡعَلُهُۥ رُكَامٗا فَتَرَى ٱلۡوَدۡقَ يَخۡرُجُ مِنۡ خِلَٰلِهِۦ وَيُنَزِّلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مِن جِبَالٖ فِيهَا مِنۢ بَرَدٖ فَيُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ وَيَصۡرِفُهُۥ عَن مَّن يَشَآءُۖ يَكَادُ سَنَا بَرۡقِهِۦ يَذۡهَبُ بِٱلۡأَبۡصَٰرِ ٤٣ يُقَلِّبُ ٱللَّهُ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّأُوْلِي ٱلۡأَبۡصَٰرِ ٤٤

43. Shin ba ka gani cewa Allah Yana kora gizagizai sannan Ya harhaɗa tsakaninsu sannan Ya mai da su masu hawan juna, sai ka ga ruwan sama yana fitowa ta tsakankaninsa, kuma Yana saukar da wasu kasake (na gizagizai) daga sama waɗanda a cikinsu akwai ƙanƙara, sai Ya sami wanda Ya ga dama da ita (ƙanƙarar) Ya kuma kautar da ita daga wanda Ya ga dama. Hasken walƙiyarsa yana kusa da ya fauce idanu.

44. Allah Yana jujjuya dare da yini. Lalle game da wannan tabbas akwai izina ga ma'abota hankula.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin Manzonsa (ﷺ) cewa yanzu bai duba ya ga yadda yake koro giza-gizai a sama ba sannan ya harhaɗa sashinsa da wani sashi, sannan ya mayar da shi

wani kan wani, daga nan sai mutum ya ga ruwa yana zubowa daga cikin wannan girgijen. Sannan ya bayyana cewa daga giza-gizan da suka haɗo a sararin samaniya manya-manya kamar duwatsu, yake saukar da ƙanƙarar ruwa ƙanana, sai ya sami wanda ya ga dama cikin bayinsa da wannan ƙanƙarar ya kuma kautar da ita daga wanda ya ga dama daga cikinsu. Hasken walƙiyar wannan girgije yana kusa da ya fauce idanu saboda tsananin haskensa. Ashe yanzu wanda ya samar da wannan giza-gizai ya koro wa bayinsa su suka saukar musu da ruwa lokacin da suke cikin buƙatarsa domin rayuwarsu ta ɗore, ashe ba shi ne ya cancanci su bauta masa ba shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba?
Sai kuma ya bayyana cewa shi ne yake jujjuya dare da rana; wannan ya zo wannan ya tafi, wani ya fi wani tsawo ko gajarta. Lalle a cikin wannan aiki nasa akwai abin izina ga masu basira, domin abin da suke ɗauke da shi na dalilai masu tabbatar da Rububiyyar Allah da Kaɗaitakarsa wajen bauta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samuwar halittu daban-daban dalili ne mai nuna cikar Ƙudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ikonsa a kan komai.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai yi nufin taƙaita dangogin tafiyar halittunsa a cikin abin da ya ambata ba, don haka ya ce: "Yana halittar abin da ya ga dama." Daga cikin abin da ya ga damar halitta kuwa akwai masu tafiya da fiye da ƙafafu huɗu kamar gizo-gizo da kyankyaso da sauransu.

Suratun Nur (45)
وَٱللَّهُ خَلَقَ كُلَّ دَآبَّةٍ مِّن مَّآءٍۖ فَمِنْهُم مَّن يَمْشِى عَلَىٰ بَطْنِهِۦ وَمِنْهُم مَّن يَمْشِى عَلَىٰ رِجْلَيْنِ وَمِنْهُم مَّن يَمْشِى عَلَىٰٓ أَرْبَعٍۚ يَخْلُقُ ٱللَّهُ مَا يَشَآءُۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٤٥﴾

45. Kuma Allah Ya halicci kowace dabba daga ruwa; sannan daga cikinsu akwai waɗanda suke jan ciki, kuma daga cikinsu akwai waɗanda suke tafiya a kan ƙafa biyu, akwai kuma waɗanda suke tafiya a kan ƙafa huɗu. Allah Yana halittar abin da Ya ga dama. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi ne ya halicci duk wani abu mai tafiya a bayan ƙasa daga ruwa, watau ɗigon maniyyi, daga cikinsu akwai waɗanda suke jan ciki kamar macizai, daga cikinsu kuma akwai masu tafiya a kan ƙafafu biyu kamar ɗan'adam da yawancin tsuntsaye, daga cikinsu kuma akwai masu tafiya da ƙafafu huɗu kamar yawancin dabbobi, don haka sassaɓawarsu a nan tare da cewa tushen abin halittarsu ɗaya ne, watau ruwan ɗigon maniyyi, yana nuna cikar Ƙudurar Allah mai yin yadda ya so, don haka ya bayyana cewa yana halittar abin da ya ga dama daga cikin abubuwan da ya ambata a nan da ma waɗanda ba a ambata ba, lalle shi mai iko ne a kan komai babu abin da zai gagare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin siffofin munafukai su dinga ƙyamar hukuncin Allah da fifita hukunce-hukunce na jahiliyya da son rai, musamman a lokacin da suka san ba su da gaskiya.

2. Bawan Allah na gaskiya shi ne mai bin gaskiya cikin abin da yake so da wanda ba ya so da abin da zai faranta masa da wanda zai baƙanta masa. Amma wanda zai yarda da hukuncin Allah don ya dace da son zuciyarsa, ya yi watsi da shi lokacin da ya saɓa wa son ransa, to wannan ba bawan Allah ne na gari ba.

3. Imani bai taƙaita a maganar baki ba kawai har sai ya haɗa da aiki, don haka Allah ya kore imani daga wanda ya juya wa hukuncinsa da na Manzonsa baya. Duk wanda bai miƙa wuyansa ga shari'ar Allah ba, to hakan alama ce da take nuna akwai wata cuta da shakku a zuciyarsa.

4. Haramun ne Musulmi ya munana zatonsa ga wani hukunci na Allah da Manzonsa, balle kuma ya ɗauke shi a matsayin rashin adalci.

5. Babu mai rabauta duniya da lahira sai wanda ya bi Allah da Manzonsa ya sallama musu cikin komai.

6. Imani da ɗa'a haƙƙi ne tsakanin Allah da Manzonsa. Tsoro da taƙawa kuwa haƙƙi ne na Allah shi kaɗai. Girmamawa da martabawa kuwa haƙƙin Manzo ne (ﷺ).

Suratun Nur (46-52)

لَّقَدۡ أَنزَلۡنَآ ءَايَٰتٖ مُّبَيِّنَٰتٖۚ وَٱللَّهُ يَهۡدِي مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٤٦ وَيَقُولُونَ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَبِٱلرَّسُولِ وَأَطَعۡنَا ثُمَّ يَتَوَلَّىٰ فَرِيقٞ مِّنۡهُم مِّنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَۚ وَمَآ أُوْلَٰٓئِكَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٤٧ وَإِذَا دُعُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ لِيَحۡكُمَ بَيۡنَهُمۡ إِذَا فَرِيقٞ مِّنۡهُم مُّعۡرِضُونَ ٤٨ وَإِن يَكُن لَّهُمُ ٱلۡحَقُّ يَأۡتُوٓاْ إِلَيۡهِ مُذۡعِنِينَ ٤٩ أَفِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ أَمِ ٱرۡتَابُوٓاْ أَمۡ يَخَافُونَ أَن يَحِيفَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ وَرَسُولُهُۥۚ بَلۡ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٥٠ إِنَّمَا كَانَ قَوۡلَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ إِذَا دُعُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ لِيَحۡكُمَ بَيۡنَهُمۡ أَن يَقُولُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ٥١ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَخۡشَ ٱللَّهَ وَيَتَّقۡهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ ٥٢

46. Haƙiƙa Mun saukar da ayoyi masu bayyana komai da komai. Allah kuma Yana shiryar da wanda Ya ga dama zuwa ga tafarki madaidaici.

47. Kuma suna cewa: "Mun yi imani da Allah da kuma Manzo kuma mun bi," sannan wata ƙungiya daga cikinsu takan ba da baya bayan wancan (imanin). Waɗannan kuwa ba muminai ba ne.

48. Idan kuwa aka yi kiran su zuwa ga Allah da Manzonsa don ya yi hukunci a tsakaninsu sai ka ga wata ƙungiya daga cikinsu suna bijirewa.

49. Idan kuwa su ne masu gaskiya sai su zo wurinsa suna masu miƙa wuya.

50. Shin cuta ce a cikin zukatansu, ko kuwa suna tababa ne, ko kuma suna tsoron Allah da Manzonsa su zalunce su ne? A'a, waɗannan su ne azzalumai.

51. Muminai ba su da wata magana idan aka kira su zuwa ga Allah da Manzonsa don ya yi hukunci a tsakaninsu sai faɗar: "Mun ji kuma mun bi." Waɗannan kuwa su ne masu babban rabo.

52. Duk kuwa wanda ya bi Allah da Manzonsa kuma yake tsoron Allah kuma yake kiyaye dokokinsa, to waɗannan su ne masu rabauta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin rahamar da ya yi wa bayinsa da ya saukar musu da littafi wanda ya ƙunshi ayoyi bayyanannu masu nuna hukunce-hukuncen shari'a da manya-manyan manufofinta da kyawawan ɗabi'u. Ya tabbatar da cewa shi ne mai shiryar da wanda ya ga dama ya ɗora shi a kan tafarki madaidaici miƙaƙƙe ɗoɗar babu karkata a tare da shi, domin ya kai shi zuwa ga shiga gidan Aljanna.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halayen munafukai waɗanda zukatansu ke cike da shakka da cutar munafurci da ƙarya, su ne masu cewa sun yi imani da Allah da Manzonsa sun kuma bi Allah da Manzonsa, to amma duk wannan magana ce ta fatar baki ba ta shiga zukatansu ba, don haka ne wata ƙungiya daga cikinsu za su ba da baya su bijire wa ɗa'a ga Allah da Manzonsa, su ƙi bin umarninsa su ƙi hanuwa daga abin da suka hana su. Sai Allah ya tabbatar da cewa waɗannan mutane ba muminai ne na gaskiya ba, ko da kuwa suna cika baki cewa sun yi imani, to ƙarya suke yi kawai.
Allah ya bayyana abin da yake tabbatar da ƙaryarsu da munafuncinsu, da cewa, idan rigima ta haɗa su da wani sai aka ce musu su zo Allah da Manzonsa su yi musu hukunci sai kawai a ga wasu suna bijire wa hukuncinsu saboda tsabar munafurci da ke cike da zukatansu. Amma fa idan su ne suke da gaskiya sai kawai a gan su da sauri sun zo wurin Manzon Allah (ﷺ) suna ƙasƙantar da kai, ba don suna son hukuncin Allah da Manzonsa ba, sai don hukuncinsu a nan ya dace da buƙatarsu da son zuciyarsu. Don haka wannan ba yabo ne a gare su ba, suka ne.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da ya jawo musu ƙin amincewa da hukuncin Allah da na Manzonsa da cewa, abin da yake cikin zukatansu na cutar munafurci da ta riga ta kama su da kuma shakkar manzancin Annabi da suke yi na ganin shi ba Manzo ne daga Allah ba, don haka ba za su bi hukuncinsa ba, ko kuma suna jin zai nuna musu irin halinsu ne ya yi musu hukunci na zalunci ba adalci ba, Allah ya tabbatar musu da cewa su ne azzalumai, domin su ne suke guje wa gaskiya da hukunci na adalci.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halayen muminai waɗanda suke yarda da hukuncin Allah da Manzonsa ko da kuwa ya saɓa wa son zuciyarsu, da cewa su duk sa'adda aka neme su su zo Allah da Manzonsa su yi musu hukunci a kan wani abu da ya faru a tsakaninsu a nan take sukan amsa su kuma ce sun ji maganar da ake faɗa musu sun kuma bi umarnin da ake ba su. Allah ya tabbatar da cewa masu irin wannan hali su ne masu rabauta duniya da lahira. Duk wanda ya bi Allah da Manzonsa ya miƙa wuya ga hukuncinsu ya ji tsoron abin da saɓon Allah zai jawo masa, ya ji tsoron azabarsa ta hanyar aiki da umarninsa da guje wa haninsa, to waɗannan ne kaɗai masu samun babban rabo a lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rantse-rantse a kan ƙarya siffa ce ta munafukai.

2. Magana babu cikawa hali ne na munafukai, wajibi ne mumini ya nisance shi.

3. Wajabcin biyayya ga Manzon Allah (ﷺ) da riƙo da sunnarsa a cikin al'amuran addini da na rayuwa gaba ɗaya.

4. Babu wata hanyar samun shiriya sai hanyar Manzon Allah. Duk wanda ya yi riƙo da koyarwarsa to lalle wannan ya shiriya, wanda ya kauce mata kuwa ya taɓe ya hallaka.

5. Babban aikin da Allah ya ɗora wa Manzonsa (ﷺ) shi ne isar da saƙo zuwa ga bayinsa, idan ya yi haka ya fita haƙƙinsu, sakamakonsu kuwa yana wajen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).n

Suratun Nur (53-54)
*وَأَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ لَئِنۡ أَمَرۡتَهُمۡ لَيَخۡرُجُنَّۖ قُل لَّا تُقۡسِمُواْۖ طَاعَةٞ مَّعۡرُوفَةٌۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ٥٣ قُلۡ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَۖ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا عَلَيۡهِ مَا حُمِّلَ وَعَلَيۡكُم مَّا حُمِّلۡتُمۡۖ وَإِن تُطِيعُوهُ تَهۡتَدُواْۚ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٥٤

53. Suka kuma rantse da Allah iya iyawarsu cewa lalle idan ka umarce su (da fita) tabbas za su fita. Ka ce (da su): "Ku daina rantse-rantse; biyayya (taku ta ƙarya) sananniya ce. Lalle Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne."

54. Ka ce (da su): "Ku bi Allah kuma ku bi Manzo; sannan idan kuka ba da baya, to lalle nauyin abin da aka ɗora masa ne kawai a kansa; kuma nauyin da aka ɗora muku yana kanku, idan kuwa kuka bi shi za ku shiriya. Ba kuwa abin da yake kan Manzo sai isar da aike mabayyani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fallasa halin munafukai da ƙaryarsu yayin da suke yin rantsuwa iyakar rantsuwarsu cewa, idan Manzon Allah (ﷺ) ya umarce su da fita jihadi don Allah, tabbas za su fita. Allah ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa su daina ma rantsuwa, domin kuwa ƙaryarsu sananna ce, hakanan cika bakinsu da sunan biyayya abu ne sananne. Saboda Allah masanin duk abin da suke aikatawa ne, ko da kuwa suna ganin sun yi shi a ɓoye ne, Allah ya sani zai kuma yi musu sakayya a kai. Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa wa waɗannan munafukan cewa su yi wa Allah da Manzonsa ɗa'a a zahirinsu da baɗininsu, idan kuwa suka kauce wa abin da aka umarce su da shi, to su sani cewa kawai nauyin da aka ɗora masa shi ne isar musu da saƙon Allah, ya kuma isar, su ma kuma nauyin da yake kansu shi ne su yi masa biyayya, su yi aiki da abin da ya zo musu da shi, to amma sun bijire masa, mummunan halinsu ya bayyana kenan. Idan kuwa suka bi Manzon Allah (ﷺ) to za su shiriya, su kama tafarki madaidaici wanda zai kai su har gidan Aljanna. Don haka zaɓi ya rage nasu. Allah kuwa shi ne mai yi musu hisabi a ranar alƙiyama ba Manzon Allah ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙawarin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) na cewa zai mayar da al'ummarsa halifofi a bayan ƙasa, watau shugabanni kuma jagororin al'ummu da yawa, waɗanda za su gyara garuruwa, su shugabanci jama'a. Da kuma alƙawarinsa na cewa zai canza musu halin tsoro da firgici da suke kwana suna tashi a cikinsa da halin aminci da zaman lafiya da za su sami damar bautar Allah ba tare da wata tsangwama ba, to ya cika wannan alƙawari da ya yi. Annabi (ﷺ) bai bar duniya ba har sai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mallaka masa garuruwan Makka da Khaibara da Bahraini da sauran garuruwan Tsibirin Larabawa, ya mallaka masa ƙasar Yaman gaba ɗayanta. Sarkin Rumawa Hiraƙlu da Muƙauƙisu Sarkin Masar da Iskandariyya da sarakunan Oman da Sarkin Habasha Najashi wanda ya karɓi mulki bayan Ashama, dukkaninsu sai da suka yi sulhun zaman lafiya da Manzon Allah (ﷺ).
Bayan rasuwarsa, Sayyadina Abubakar ya karɓi ragamar jagorancin al'ummar Musulmi, ya kuma yi aiki tuƙuru wajen ɗinke ɓarakar da ta auku a cikinsu. Ya aika da rundunar mayaƙa a ƙarƙashin jagorancin Khalid ɗan Walid zuwa garuruwan Farisawa, ya yi nasarar cin wasu garuruwansu da yaƙi. Ya kuma aika da wata rundunar zuwa ƙasar Sham ƙarƙashin jagorancin Abu Ubaidata ɗan Jarrah (Allah ya ƙara masa yarda) da wata runduna ta uku ƙarƙashin jagorancin Amru ɗan Asi zuwa ƙasar Masar, dukkaninsu suka sami nasarar buɗe wasu garuruwa na waɗannan ƙasashe.
A zamanin Sayyadina Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) kuwa wanda ya gaji halifanci daga Sayyadina Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) bayan rasuwarsa, shi ma ya yi gagarumin aiki, Allah ya ba shi nasarori masu tarin yawa a kan manyan maƙiyansa. A lokacin ne aka gama karɓe garuruwan Sham gaba ɗayansu daga hannun daular Rumawa, hakanan ya ƙwace gaba ɗayan garuruwan Masar, ya kuma cinye akasarin garuruwan Farisa da yaƙi.
A zamanin halifancin Sayyadina Usman (Allah ya ƙara masa yarda) kuma shugabancin Musulmi ya ƙara faɗaɗa a duniya, ikonsu ya shimfiɗu a gabashin duniya da yammacinta, ya kai har zuwa ƙasar Andalus da Ƙubrus da garuruwan Ƙairawan ta ɓangaren yamma. A nahiyar gabas kuwa sai da mulkin Musulmi ya kai garuruwan ƙasar Sin, watau Chana.

An karɓo daga Saubanu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah ya tattaro mini duniya wuri guda sai na ga gabashinta da yammacinta, kuma lalle sai mulkin al'ummata ya kai inda aka tattaro mini daga gare ta." [Muslim #2889].

An karɓo daga Tamimuddari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle wannan al'amari (Musulunci) sai ya kai duk inda dare da rana suka kai, Allah ba zai bar wani gidan laka ko na gashin raƙuma ba (watau birni da ƙauye) face sai ya shigar da wannan addini a cikinsa da izzar Mai Izza ko da ƙaskancin ƙaskantacce; izzar da Allah zai ɗaukaka Musulunci da ita da ƙaskancin da zai ƙaskantar da kafirci da shi." [Ahmad #16957].

2. An karɓo daga Abul Aliya (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya shekara fiye da goma a Makka yana kira zuwa ga Allah da bautarsa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba, shi da sahabbansa, a ɓoye kuma cikin tsoro. Ba a kuma umarce su da yin jihadi ba har sai bayan da suka yi hijira zuwa Madina sannan Allah ya umarce shi da yaƙi, sai suka kasance cikin tsoro koyaushe, safe da yamma suna ɗauke da makamansu, suka zama tsawon wani lokaci a haka, har wani daga cikin sahabbai ya ce: "Yanzu haka za mu yi ta zama cikin tsoro har abada? Yanzu babu wata rana kenan da za ta zo da za mu jingine waɗannan makaman mu ma mu sami aminci?" Sai Manzon Allah ya ce masa: "Ku yi haƙuri, nan ba da daɗewa ba sai ɗayanku ya zauna a cikin babban taro ya harɗe babu wani mai riƙe da makami a wurin." [Ibn Kasir, juzu'i na 6, shafi na 79].

3. Wannan alƙawari na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga Musulmi yana nan har zuwa ranar tashin alƙiyama, matuƙar dai za su cika sharaɗin da Allah ya gindaya musu don samun wannan kafuwar; watau su yi imani da Allah imani na gaskiya, su kuma yi ayyuka na gari. Allah kuma ba ya saɓa alƙawari.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da muminai cewa idan har ya kafa su a bayan ƙasa to wajibi ne su ƙara ƙoƙari wajen bautar sa, musamman su tsayar da salloli da fitar da zakkar dukiyoyinsu da yi wa Allah da Manzonsa ɗa'a cikin al'amuransu gaba ɗaya, domin da haka ne za su sami rahamar Allah.

Suratun Nur (55-57)

وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَيَسۡتَخۡلِفَنَّهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ كَمَا ٱسۡتَخۡلَفَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ وَلَيُمَكِّنَنَّ لَهُمۡ دِينَهُمُ ٱلَّذِي ٱرۡتَضَىٰ لَهُمۡ وَلَيُبَدِّلَنَّهُم مِّنۢ بَعۡدِ خَوۡفِهِمۡ أَمۡنٗاۚ يَعۡبُدُونَنِي لَا يُشۡرِكُونَ بِي شَيۡـٔٗاۚ وَمَن كَفَرَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٥٥ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٥٦ لَا تَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مُعۡجِزِينَ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَمَأۡوَىٰهُمُ ٱلنَّارُۖ وَلَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ٥٧

55. Allah kuwa Ya yi wa waɗanda suka yi imani daga cikinku suka kuma yi aiki na gari alƙawarin lalle zai sanya su halifofi a bayan ƙasa kamar yadda Ya sanya waɗanda suke gabaninsu halifofi, kuma lalle zai tabbatar musu da addininsu wanda Ya yardar musu, tabbas kuma zai dawo musu da zaman lafiya bayan zamantowarsu cikin tsoro. Su bauta mini, ba sa yin shirkar komai da Ni. Wanda kuwa ya kafirta bayan wannan, to waɗannan su ne fasiƙai.

56. Kuma ku tsai da salla ku kuma ba da zakka kuma ku bi Manzo don a ji ƙan ku.

57. Kada kuma ka tsammaci waɗanda suka kafirta za su gagara a bayan ƙasa, kuma makomarsu wuta ce; makoma kuwa ta munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawari ga muminai waɗanda suka yi imani da Allah suka kuma yi ayyuka na gari da cewa zai ba su nasara a kan maƙiyansu, ya mayar da su halifofi a bayan

ƙasa kamar yadda ya mayar da muminan farko halifofi, watau kamar mutanen Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan hallakar da Fir'auna da rundunarsa. Hakanan ya yi musu alƙawarin zai tabbatar musu da addininsu wanda ya yarje musu, watau Musulunci ya zama addini mai izza da daraja, sannan kuma ya canja musu tsoron da suke rayuwa a cikinsa da zaman lafiya da kwanciyar hankali su yi ta bautar Allah shi kaɗai ba tare da suna haɗa shi da komai ba.
Amma kuma ya gargaɗe su da cewa, duk wanda ya kafirce wa waɗannan ni'imomin na Allah daga baya, to waɗannan su ne fasiƙai masu kauce wa ɗa'a ga Allah da yin ɓarna a bayan ƙasa bayan gyaranta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya umarci muminai da su tsayar da salla yadda ya kamata su kuma bayar da zakkar dukiyoyinsu, sannan su bi Manzon Allah ta hanyar aiki da umarninsa da guje wa haninsa, don da wannan ne kawai za su sami rahamar Allah.
Sai kuma ya lallashi Manzonsa da cewa kar ya zaci cewa waɗanda suka kafirce wa Allah, suka riƙa yaƙar sa da mabiyansa, za su gagare shi ko su kuɓuce masa lokacin da ya yi niyyar saukar musu da azabarsa, Allah ba zai ƙyale su haka ba sai ya nuna musu mummunan ƙarshensu, ya kuma tabbatar masa da cewa makomarsu a ranar alƙiyama wutar Jahannama ce, kuma tir da wannan makoma tasu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yara ƙanana sun kasu gida uku wajen neman izini:
Na farko, yaran da ba sa fahimtar komai da ya danganci mata, to waɗannan babu neman izini a kansu a kowane lokaci.
Na biyu, yaran da suka fara fahimtar al'amarin mata, to waɗannan akwai buƙatar su nemi izini a waɗannan lokuta uku da aka ambata a ayar, ban da sauran lokuta.
Na uku su ne waɗanda suka balaga; to waɗannan akwai buƙatar su nemi izini a kowane lokaci za su shiga inda iyayensu suke.

2. Iyayen yara da waɗanda suka mallaki bayi da barori wajibi ne a kansu su koyar da su ladubban shari'a da zamantakewa.

3. Lura da kiyaye tsiraici abu ne mai muhimmanci ga Musulmi.

4. Musulmi a da sun saba da barcin ƙailula, watau wanda ake yi gabanin sallar Azahar da ɗan lokaci kaɗan, shi ya sanya Allah ya yi musu bayanin wannan al'amari da suka saba da shi.

5. Babu laifi a sanya yara ayyukan da ba za su wahalar da su ba.

6. Balagar yaro takan tabbata ne ta hanyar fitar da maniyyi daga gare shi a barci ko a farke.7. Halaccin mata tsofaffi su sassauta lullubinsu domin babu wata fitina a tattare da su.

Suratun Nur (58-60)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لِيَسۡتَـٔۡذِنكُمُ ٱلَّذِينَ مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُمۡ وَٱلَّذِينَ لَمۡ يَبۡلُغُواْ ٱلۡحُلُمَ مِنكُمۡ ثَلَٰثَ مَرَّٰتٖۚ مِّن قَبۡلِ صَلَوٰةِ ٱلۡفَجۡرِ وَحِينَ تَضَعُونَ ثِيَابَكُم مِّنَ ٱلظَّهِيرَةِ وَمِنۢ بَعۡدِ صَلَوٰةِ ٱلۡعِشَآءِۚ ثَلَٰثُ عَوۡرَٰتٖ لَّكُمۡۚ لَيۡسَ عَلَيۡكُمۡ وَلَا عَلَيۡهِمۡ جُنَاحُۢ بَعۡدَهُنَّۚ طَوَّٰفُونَ عَلَيۡكُم بَعۡضُكُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖۚ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلۡأٓيَٰتِۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٥٨ وَإِذَا بَلَغَ ٱلۡأَطۡفَٰلُ مِنكُمُ ٱلۡحُلُمَ فَلۡيَسۡتَـٔۡذِنُواْ كَمَا ٱسۡتَـٔۡذَنَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمۡ ءَايَٰتِهِۦۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٥٩ وَٱلۡقَوَٰعِدُ مِنَ ٱلنِّسَآءِ ٱلَّٰتِي لَا يَرۡجُونَ نِكَاحٗا فَلَيۡسَ عَلَيۡهِنَّ جُنَاحٌ أَن يَضَعۡنَ ثِيَابَهُنَّ غَيۡرَ مُتَبَرِّجَٰتِۭ بِزِينَةٖۖ وَأَن يَسۡتَعۡفِفۡنَ خَيۡرٞ لَّهُنَّۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٦٠

58. Ya ku waɗanda suka yi imani, bayinku da kuma waɗanda ba su isa mafarki ba a cikinku (watau waɗanda ba su balaga ba) su nemi izininku sau uku. Kafin sallar Asuba da sanda kuke tuɓe tufafinku a lokacin garjin rana da kuma bayan sallar Lisha. Lokatai ne guda uku na tsiraicinku. Babu laifi a kanku ko a kansu bayansu (waɗannan lokatai). Masu shige da fice ne a gare ku sashinku bisa sashi. Kamar haka ne Allah Yake bayyana muku ayoyi. Allah kuma Masani ne, Mai hikima.

59. Idan kuma yara daga cikinku suka isa mafarki (watau suka balaga) sai su nemi izini kamar yadda waɗanda suke gabaninsu suka riƙa neman izini. Kamar haka Allah Yake bayyana muku ayoyinsa. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima.

60. Tsofaffin mata kuwa waɗanda ba sa tsammanin yin aure to babu laifi a kansu su sauke lullubinsu, amma ba masu fitar da adonsu ba; amma kuma su yi lullubi shi ya fi zama alheri a gare su. Allah kuwa Mai ji ne, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukunce-hukunce na neman izinin shiga gidaje daga bayi da barori da ƙananan yara waɗanda ba su balaga ba. Allah ya kirawo muminai waɗanda suka yi imani da Allah suke aiki da shari'arsa, ya umarce su da su koya wa bayinsu maza da mata da 'ya'yansu waɗanda ba su balaga ba cewa, su nemi izinin shiga wurarensu a lokuta guda uku. Na farko, kafin sallar Asuba lokacin da suke canza tufafin barcinsu su sanya tufafin zaman gida. Na biyu, lokacin barcin ƙailula na Azahar yayin da suke cire tufafinsu su sanya na kwanciya domin hutawa. Na uku, bayan sallar Lisha, domin lokaci ne da suke cire tufafinsu su saka tufafin barci. Allah ya bayyana cewa waɗannan lokuta ne guda uku na tsiraicinsu, don haka kada yaran su shiga inda suke sai sun nemi izininsu.
Sai kuma ya bayyana cewa sauran lokutan kuma da ba waɗannan ukun ba, babu wani laifi a kansu ko a kan yaran su shiga inda suke ba tare da sun nemi izinin shigowa ba, domin su masu yawan shigi da fici ne gare su, domin buƙatarsu da yi musu hidima. Don haka kallafa musu neman izini yayin shiga wajensu a kowane lokaci akwai matsawa a gare su da ma su magidantan baki ɗaya. Allah ya bayyana cewa kamar yadda ya yi musu bayanin hukunce-hukuncen neman izini, to hakanan yake bayyana musu ayoyinsa masu nuna musu hukunce-hukuncen da ya shar'anta musu. Allah masani ne ga duk wata maslaha da ta danganci bayinsa, mai hikima ne cikin duk abin da ya shar'anta musu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da su cewa idan 'ya'yansu ƙanana suka balaga, to lallai su nemi izninsu duk sanda suka tashi shiga inda suke a kowane lokaci kamar yadda aka yi bayanin wannan hukuncin a baya game da manya. Kamar yadda Allah ya yi wannan bayanin a nan, to hakanan yake bayyana musu ayoyinsa, kuma shi masani ne ga duk wata maslaha ta bayinsa, mai hikima ne cikin hukunce-hukuncensa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin lullubin mata tsofaffi tukuf, waɗanda saboda tsufa ma sun daina al'ada balle ɗaukar ciki, waɗanda ba sa tsammanin wani aure, to waɗannan babu laifi a kansu idan sun sassauta lullubinsu kamar mayafi ko nikabi ba kuma tare da sun fito cikin kwalliya ba, to amma dai su yi lullubin cikakke shi ne ya fi musu alheri. Allah mai jin komai ne, masanin ayyukan kowa, don haka zai yi wa kowa sakayya daidai aikinsa mai kyau da maras kyau.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Uzuri sababi ne da kan sanya a samu sassauci a kan wasu hukunce-hukunce.

2. Musulunci addini ne da babu tsanantawa a cikinsa. Kowa ana ɗora masa aikin da zai iya ne, wanda kuwa ba zai iya ba ana yi masa rangwame a kansa.

3. Dukkan wani abu da yake buƙatar neman izinin mai abin, ana tabbatar da izininsa ta hanyar ya furta da bakinsa ko kuma al'ada ta nuna samuwar wannan izinin ko da kuwa ba a furta shi ba. Kamar cin abincin gidajen da aka ambata, bisa ga al'adar zamantakewa ba a tsayawa neman izini daga masu waɗannan gidaje gabanin waɗannan masu dangantaka da su su ci abincin gidansu.

4. Halaccin cin abinci tare ko kuma daban-daban, amma ci tare ya fi albarka.5. Falalar sallama ga Musulmi a junansu.

Suratun Nur (61)

لَّيْسَ عَلَى ٱلْأَعْمَىٰ حَرَجٌ وَلَا عَلَى ٱلْأَعْرَجِ حَرَجٌ وَلَا عَلَى ٱلْمَرِيضِ حَرَجٌ وَلَا عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمْ أَن تَأْكُلُوا۟ مِنۢ بُيُوتِكُمْ أَوْ بُيُوتِ ءَابَآئِكُمْ أَوْ بُيُوتِ أُمَّهَٰتِكُمْ أَوْ بُيُوتِ إِخْوَٰنِكُمْ أَوْ بُيُوتِ أَخَوَٰتِكُمْ أَوْ بُيُوتِ أَعْمَٰمِكُمْ أَوْ بُيُوتِ عَمَّٰتِكُمْ أَوْ بُيُوتِ أَخْوَٰلِكُمْ أَوْ بُيُوتِ خَٰلَٰتِكُمْ أَوْ مَا مَلَكْتُم مَّفَاتِحَهُۥٓ أَوْ صَدِيقِكُمْ ۚ لَيْسَ عَلَيْكُمْ جُنَاحٌ أَن تَأْكُلُوا۟ جَمِيعًا أَوْ أَشْتَاتًا ۚ فَإِذَا دَخَلْتُم بُيُوتًا فَسَلِّمُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمْ تَحِيَّةً مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ مُبَٰرَكَةً طَيِّبَةً ۚ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلْءَايَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿٦١﴾

61. Babu wani laifi a kan makaho, babu kuma wani laifi a kan gurgu, kuma babu wani laifi a kan marar lafiya ko kuma a kanku, kan ku ci a gidajenku ko a gidajen iyayenku maza ko a gidajen iyayenku mata ko a gidajen 'yan'uwanku maza ko a gidajen 'yan'uwanku mata ko a gidajen baffanninku ko a gidajen gwaggwanninku ko kuma a gidajen kawunnanku ko kuma a gidajen yagwalgwalanku, ko kuma abin da kuka mallaki mabuɗansa, ko kuma na abokinku. Babu wani laifi a kanku ku ci tare ko kuma daban-daban, sannan idan za ku shiga gidaje sai ku yi wa junanku sallama, (wannan) gaisuwa ce daga wurin Allah mai albarka tsattsarka. Kamar haka Allah Yake bayyana muku ayoyi don ku hankalta.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin sauƙin da ya yi wa masu larura kan wasu ayyuka na wajibi waɗanda ba za su iya aikatawa ba saboda larurarsu, Allah ya bayyana cewa babu wani laifi a kan makaho da ba ya gani da gurgu da marar lafiya idan sun zamanto ba za su iya wasu ayyuka na wajibi ba kamar jihadi.
Sai kuma ya bayyana wa muminai hukuncin cin abinci a wasu gidajen da ba nasu ba, da cewa, babu laifi a kansu su ci abinci a gidansu kamar gidajen 'ya'yansu, ko su ci a gidan iyayensu maza ko mata ko a gidan 'yan'uwansu maza da mata ko kuma a gidajen kawunnansu maza da mata ko a gidajen yagwalgwalansu mazansu da matansu ko kuma a cikin gidajen da aka danƙa kula da su a hannunsu, kamar mai gadin lambu. Hakanan babu laifi su ci a gidajen abokansu domin bisa ga al'ada wannan abu ne da babu wata damuwa a cikinsa.
Sannan ya bayyana cewa babu laifi 'yan gida ɗaya su haɗu su ci a kwano ɗaya, ko kuma su rarrabu kowa ya ci a kwanonsa.

An karɓo daga Wahshi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya koka wa Manzon Allah (ﷺ) cewa suna cin abinci amma ba sa ƙoshi, sai Manzon Allah ya ce masa: "Watakila kuna ci ne daban-daban; ku haɗu tare ku ci abincinku, ku kuma ambaci sunan Allah a kansa, za a sanya muku albarka a cikinsa." [Ahmad #16078 da Abu Dawuda #3764 da Ibn Majah #3286].

An karɓo daga Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Abincin da Allah ya fi so shi ne wanda hannaye suka yawaita a kansa." [Abu Ya'ala #2045 da Tabarani, Al-Ausat #7313].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da yin sallama ga junansu a duk lokacin da suka zo shiga gidajensu ko gidajen wasu, watau su ce: "*Assalamu Alaikum*." Idan kuwa babu kowa a gidan sai su

ce: "*Assalamu Alaina Wa Ala Ibadillahis Salihin*." Allah ya nuna musu cewa wannan gaisuwa ce mai albarka daga Allah da ya shar'anta musu ita saboda za ta haifar musu da soyayya da ƙarin danƙon zumunci a junansu, kuma tsarkakakkiya ce da take tsarkake zuciyar duk mai yin ta ko wanda ake yi masa ita. Allah ya ambata musu cewa irin waɗannan bayanai da ya yi musu a wannan Sura, to hakanan yake bayanin ayoyinsa ga mutane domin su fahimce su su yi aiki da su a rayuwarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin martabar Manzon Allah (ﷺ) da wajabcin girmama shi.

2. Muhimmancin haɗuwar Musulmi su yi aiki tare a ƙarƙashin jagoranci guda ɗaya.

3. Muhimmanci da wajabcin girmama shugaba da yi masa biyayya a kan abin da zai tabbatar da maslahar al'umma.

4. Wannan hukunci na neman izinin fita lokacin da ake taro bai taƙaita ga Annabi (ﷺ) ba kawai, ya shafi duk wani shugaba na Musulmi wanda zai zauna don tattauna abin da zai ciyar da Musulunci da Musulmi gaba.

5. Kiran tsurar sunan Manzon Allah (ﷺ) ba tare da lafuzzan girmamawa ba bai halatta ba a koyaushe.

6. Wajabcin yi wa Manzon Allah (ﷺ) biyayya da haɗarin da yake tattare da saɓa masa na aukawa cikin fitina ta kauce wa addini, ko wata azaba mai raɗaɗi.

Suratun Nur (62-64)

إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَإِذَا كَانُواْ مَعَهُۥ عَلَىٰٓ أَمۡرٖ جَامِعٖ لَّمۡ يَذۡهَبُواْ حَتَّىٰ يَسۡتَـٔۡذِنُوهُۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسۡتَـٔۡذِنُونَكَ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۚ فَإِذَا ٱسۡتَـٔۡذَنُوكَ لِبَعۡضِ شَأۡنِهِمۡ فَأۡذَن لِّمَن شِئۡتَ مِنۡهُمۡ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لَهُمُ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٦٢ لَّا تَجۡعَلُواْ دُعَآءَ ٱلرَّسُولِ بَيۡنَكُمۡ كَدُعَآءِ بَعۡضِكُم بَعۡضٗاۚ قَدۡ يَعۡلَمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ يَتَسَلَّلُونَ مِنكُمۡ لِوَاذٗاۚ فَلۡيَحۡذَرِ ٱلَّذِينَ يُخَالِفُونَ عَنۡ أَمۡرِهِۦٓ أَن تُصِيبَهُمۡ فِتۡنَةٌ أَوۡ يُصِيبَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٦٣ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ قَدۡ يَعۡلَمُ مَآ أَنتُمۡ عَلَيۡهِ وَيَوۡمَ يُرۡجَعُونَ إِلَيۡهِ فَيُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُواْۗ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمُۢ ٦٤

62. Muminai na haƙiƙa (su ne) waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, idan kuma suka kasance tare da shi bisa wani al'amari na jama'a, to ba za su tafi ba har sai sun nemi izininsa. Lalle waɗanda suke neman izininka waɗannan (su ne) waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa. To idan sun nemi izininka saboda wani sha'aninsu, sai ka yi izini ga wanda ka ga dama daga cikinsu, kuma ka nema musu gafarar Allah. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai rahama.

63. Kada ku mayar da kiran Manzo a tsakaninku kamar kiran junanku ga juna. Haƙiƙa Allah Yana sane da waɗanda suke zare jiki daga cikinku a ɓoye. To lalle waɗanda suke saɓa wa umarninsa su ji tsoron kada wata fitina ta shafe su ko kuma wata azaba mai raɗaɗi ta same su.

64. Ku saurara, lalle abin da yake sammai da ƙasa na Allah ne; haƙiƙa Yana sane da abin da ku kuke kansa, da kuma ranar da za a komar da su zuwa gare Shi, sannan Ya ba su labarin abin da suka aikata. Allah Masanin komai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai wani ladabin na musamman, watau neman izini lokacin da suka so fita daga wajen taron da suke yi da Manzon Allah (ﷺ), kamar yadda ya bayyana musu ladabin neman izininsa idan sun zo shiga wajensa.
Allah ya bayyana cewa muminai na gaskiya su ne waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa (ﷺ); idan kuma suna tare da Manzon Allah a wurin wani taro da ya haɗa su don neman shawara ko tattauna wata maslaha ta addini ko ta al'umma, to kada wani ya bar wurin wannan taro har sai ya nemi izini daga wurin Manzon Allah (ﷺ). Allah ya tabbatar wa Manzonsa cewa waɗannan da suke neman izininsa domin fita daga wurin taro saboda wani uzuri da ya taso musu su ne waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa (ﷺ) imani na haƙiƙa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzon Allah (ﷺ) da cewa idan wani daga cikinsu yana cikin wani uzuri yana buƙatar a yi masa izini don sauke wannan uzurin nasa, to Annabi (ﷺ) ya yi wa wanda ya ga dama daga cikinsu izinin tafiya idan ya fahimci yana da ƙaƙƙarfan uzuri da zai sa ya tafi ya bar taron. Sannan ya umarce shi da ya nema musu gafarar Allah domin akwai yiwuwar samun gazawa cikin uzurin da wasu za su bijiro da shi har Annabi (ﷺ) ya yi musu izini ba tare da sun cancanci hakan ba, Allah yana gafarta zunubban waɗanda suka tuba daga cikin bayinsa, yana jin ƙan su da rahama.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai wani haƙƙi na Manzon Allah a kansu wanda yake nuna girmamawa gare shi, da cewa, kada su riƙa kiran sa da tsurar sunansa, watau ɗayansu ya riƙa cewa 'Ya Muhammadu' ko 'Ya Muhammadu ɗan Abdullahi' ko 'Ya ɗan Abdullahi', kamar dai yadda suke kiran junansu. Idan za su kira shi su ce: 'Ya Manzon Allah' ko 'Ya Annabin Allah'. Hakanan idan ya kirawo su wani taro, to kada su ɗauki kiransa da rashin muhimmanci kamar yadda suke ɗaukar kiraye-kirayen junansu. Su gaggauta amsa kiransa. Allah ya tabbatar musu da cewa ya san waɗanda suke zare jiki daga cikinsu su fita daga wurin taro ba tare da sun nemi izinin Manzon Allah (ﷺ) ba, don haka sai ya gargaɗe su da cewa, lalle masu saɓa wa umarnin Manzon Allah (ﷺ) su shiga taitayinsu kada wani bala'i ya auka musu ko kuma wata azaba mai raɗaɗî ta same su a sanadiyyar saɓa umarninsa.
Sai kuma Allah (ﷻ) ya rufe Surar da bayyana cewa duk abin da yake cikin sammai da wanda yake bayan ƙasa halittarsa ne, mulkinsa ne, ƙarƙashin gudanarwarsa yake, don haka ya san duk wani hali da bayinsa suke ciki kuma ranar alƙiyama, ranar da za a mayar da su wajensa zai ba su dukkan labaran abin da suka aikata a duniya, domin shi masanin komai ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ni'imomin Allah da albarkatunsa alamomi ne masu nuna kamalar Rububiyyarsa.

2. Saukar da Alƙur'ani yana daga cikin manya-manyan albarkatun Allah da ni'imominsa ga bayinsa.

3. Annabi Muhammadu (ﷺ) Manzo ne zuwa ga dukkan talikai; mutum da aljan.

4. Alƙur'ani littafi ne da ke rarrabe tsakanin ƙarya da gaskiya.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya da ɗa ko abokin tarayya, don haka ba zai taɓa yarda da masu jingina masa ɗa ko abokin tarayya ba.

6. Komai da Allah ya halitta ya halicce shi ne bisa ga hikima da ilimi, ya kuma yi shi gwargwadon yadda ya dace babu wata tangarɗa cikin aikinsa.

25-Suratul Furƙan

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da *'Suratul Furƙan'* tun zamanin Manzon Allah (ﷺ) , kamar yadda Imamul Bukhari [#2419] da Imamu Muslim [#818] suka ruwaito daga Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Hisham ɗan Hakim ɗan Hizam yana karanta *Suratul Furƙan* saɓanin yadda nake karanta ta, kuma ni Manzon Allah ne ya karantar da ni ita, sai na yi kusa in far masa amma sai na ɗan saurara masa har ya gama, sai na cukuikuye shi da mayafinsa na kai shi gaban Manzon Allah (ﷺ) na ce: Na ji shi ne yana karanta *Suratul Furƙan* saɓanin yadda ka karantar da ni. Sai Manzon Allah ya ce mini: "Sake shi." Sannan sai ya ce masa: "To kai karanta." Sai ya karanta. Sai ya ce: "Kamar haka aka saukar da ita." Sannan ya ce da ni: "Kai ma karanta." Sai na karanta. Sai ya ce: "Kamar haka aka saukar da ita. Lalle an saukar da Alƙur'ani bisa haruffa bakwai, don haka ku karanta abin da ya sawwaƙa daga gare shi."
An kuma kira ta ne da *'Suratul Furƙan'* domin an ambaci wannan lafazi "*Alfurƙan*" a ayarta ta farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai sun yarda da cewa wannan Sura Makkiyya ce, watau an saukar da ita gabanin hijira zuwa Madina. Amma an ruwaito daga Abdullahi ɗan Abbas cewa, ya togace ayoyi uku daga cikinta, watau daga aya ta 68 zuwa ta 70. Sai dai abin da ya inganta daga gare shi shi ne, waɗannan ayoyi duka *Makkiyya* ne.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba'in da biyu (42) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan Suratu Yasin gabanin *Suratu Faɗir*.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta saba'in da bakwai (77) ne babu saɓani tsakanin makaranta a kan haka.

5. Babban Jigonta:
Lallashin Manzon Allah (ﷺ) game da muzgunawar da yake fuskanta daga mushirikan Makka.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• An buɗe ta da yabon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da nuna girman Alƙur'ani.
• Surar ta ginu ne a kan ginshiƙai uku:
Na farko, tabbatar da cewa Alƙur'ani saukakke ne daga Allah, da nuna girman Manzon Allah (ﷺ) wanda aka saukar wa da Alƙur'ani da bayanin dalilan da suke tabbatar da gaskiyarsa, tare da nuna gudun duniyarsa, da bayyana kasancewarsa yana bin tafarki irin na annabawan da suka gabace shi.
Na biyu, tabbatar da tashin alƙiyama da sakamakon ayyuka, da yi wa mutanen ƙwarai albishir da kyakkyawan sakamako da gargaɗin mushirikai da mummunan sakamakon da yake jiran su a wannan ranar.
Na uku, kafa dalilai a kan Kaɗaitakar Allah wajen bauta da halitta, da tsarkake shi daga riƙon ɗa ko abokin tarayya, da nuna ɓacin bautar gumaka ba Allah ba.

• Lallashin Annabi Muhammadu (ﷺ) da ƙarfafa masa gwiwa a kan kiran da yake yi zuwa ga Allah da fuskantar tirjiyar kafirai a gare shi.
• Ba shi labaran annabawa tare da al'ummunsu don ya yi haƙuri da juriya kamar yadda su ma suka yi.
• Yaba wa muminai na ƙwarai da bayyana wasu daga cikin kyawawan halayensu, waɗanda saboda su ne suka cancanci gidan Aljanna.

Suratul Furƙan (1-2)
تَبَارَكَ ٱلَّذِى نَزَّلَ ٱلْفُرْقَانَ عَلَىٰ عَبْدِهِۦ لِيَكُونَ لِلْعَٰلَمِينَ نَذِيرًا ۝١ ٱلَّذِى لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَلَمْ يَتَّخِذْ وَلَدًا وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ شَرِيكٌ فِى ٱلْمُلْكِ وَخَلَقَ كُلَّ شَىْءٍ فَقَدَّرَهُۥ تَقْدِيرًا ۝٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. (Allah) Wanda Ya saukar wa Bawansa Alƙur'ani don ya zamo mai gargaɗi ga talikai albarkatunsa sun yawaita.

2. (Shi ne) Wanda mulkin sammai da ƙasa nasa ne, kuma bai riƙi wani ɗa ba, ba kuma Shi da wani abokin tarayya a cikin mulkin, Ya kuma halicci kowanne abu, sannan Ya ajiye shi a irin gwargwadon da ya dace da shi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da tabbatar da cewa shi ne wanda alheransa da albarkatunsa suke da yawa; mafi girmansu kuwa shi ne saukar da Alƙur'ani da ya yi ga bawansa Annabi Muhammadu (ﷺ) . Wannan Alƙur'ani kuwa shi ne mai rarrabe tsakanin ƙarya da gaskiya. Ya saukar masa da shi kuma don ya zamanto mai gargaɗi ga talikai mutane da aljannu ya kuma tsoratar da su azabar Allah.
Sannan Allah ya bayyana girmansa da yalwar mulkinsa da cewa shi ne kaɗai mamallakin sammai da ƙasa, dukkansu halittarsa ne kuma bayinsa ne kuma a ƙarƙashin ikonsa suke. Kuma ba shi da ɗa ko wani abokin tarayya tare da shi a mulkinsa. Shi ne ya halicci komai ya ƙaddara halittarsu daidai gwargwadon hikimarsa da iliminsa, watau ya ajiye komai inda ya dace da shi.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da rashin cancantar duk wani abin bauta ba Allah ba.

2. Karancin hankalin masu bautar wasu ba Allah ba duk da suna ganin tawayarsu.

Suratul Furƙan (3)
وَٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً لَّا يَخْلُقُونَ شَيْـًٔا وَهُمْ يُخْلَقُونَ وَلَا يَمْلِكُونَ لِأَنفُسِهِمْ ضَرًّا وَلَا نَفْعًا وَلَا يَمْلِكُونَ مَوْتًا وَلَا حَيَوٰةً وَلَا نُشُورًا ۝٣

3. Kuma suka riƙi ababen bauta ba Shi ba, ba sa halittar komai, alhali kuwa su ake halittawa, kuma ba sa mallakar cuta ko amfani ga kawunansu, ba sa kuma mallakar kashewa ko rayawa ko tashi (bayan mutuwa).
A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mushirikai sun riƙi wasu abubuwan bauta ba Allah ba, waɗanda suke ɗauke da tawaya ta fuskoki da dama, daga cikinsu ya ambaci huɗu:
Na farko, ba sa iya halittar komai komin ƙanƙantarsa. Abin bauta kuwa dole ne ya zama mai ikon halitta.
Na biyu, su halittu ne, duk wani mahaluƙi kuwa mabuƙaci ne. Abin bauta kuma dole ne ya zamo mawadaci ba mabuƙaci ba.

Na uku, ba sa mallakar wa kawunansu cuta ko amfani ballantana ga wani. Duk mai irin wannan siffar bai dace a bauta masa ba.
Na huɗu, ba su da ikon sarrafa komai, domin ba sa iya kashewa ko rayawa ko tayar da matattu bayan mutuwarsu. Don haka ta ƙaƙa za a kirawo su abin bauta?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zargin Manzon Allah da yi wa Allah ƙarya abu ne da su kansu kafirai sun san ba gaskiya ba ne, domin sun san Manzon Allah (ﷺ) tun tasowarsa mutum ne mai gaskiya da riƙon amana, ba su taɓa kama shi da yi wa wani daga cikinsu ƙarya ba, to ta ƙaƙa zai yi wa Allah ƙarya?!

2. Su kansu kafirai sun tabbatar cewa zarginsu ga Manzon Allah (ﷺ) na cewa yana rubuta tatsuniyoyin mutanen farko yana cewa Alƙur'ani ne, wannan zargi nasu ƙanzon kurege ne, domin sun san ba ya karatu ba ya rubutu, to ta yaya zai iya rubuta wani abu daga littattafan farko?!

3. Da a ce wasu ne suka taimaka wa Manzon Allah (ﷺ) ya ƙirƙiri Alƙur'ani kamar yadda suke zargi, to da sun iya kawo wani ƙirƙirarren abu kamarsa, kamar yadda Allah ya ƙalubalance su da su aikata, amma suka kasa. Wannan kaɗai ya isa ya tabbatar da ƙaryarsu da rashin hankalinsu.

4. Allah ya bayyana musu cewa shi ne ya saukar da Alƙur'ani, kuma shi ne masanin sirrin sammai da ƙasa, don ya tabbatar musu da cewa, ba zai yiwu wani mahaluƙi ya ƙagi wannan Alƙur'ani ya jingina masa ba, ya kuma yaƙi waɗanda suka ƙi yin imani da shi ya halatta jininsu da dukiyarsu da hujjar cewa Allah ne ya umarce shi da haka. Kuma Allah ya san komai amma duk da haka ya yi ta ƙarfafa gwiwar Manzonsa (ﷺ) yana ba shi nasara a kan maƙiyansa, yana mallaka masa garuruwa. Wannan abu ne da a hankalce ba zai yiwu ba.

5. Faffaɗar rahamar Allah da ya kasance mai karɓar tuban wanda ya tuba daga cikin bayinsa daga kowane irin laifi, ya kuma yi masa rahama.

Suratul Furƙan (4-6)
وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّآ إِفۡكٌ ٱفۡتَرَىٰهُ وَأَعَانَهُۥ عَلَيۡهِ قَوۡمٌ ءَاخَرُونَۖ فَقَدۡ جَآءُو ظُلۡمٗا وَزُورٗا ۝٤ وَقَالُوٓاْ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٱكۡتَتَبَهَا فَهِيَ تُمۡلَىٰ عَلَيۡهِ بُكۡرَةٗ وَأَصِيلٗا ۝٥ قُلۡ أَنزَلَهُ ٱلَّذِي يَعۡلَمُ ٱلسِّرَّ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ إِنَّهُۥ كَانَ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ۝٦

4. Waɗanda kuma suka kafirta suka ce: "Wannan (Alƙur'ani) ba komai ba ne sai ƙarya da ya ƙage ta kuma wasu mutane daban suka taimake shi a kansa." To haƙiƙa sun zo da zalunci da kuma ƙarya.

5. Suka kuma ce: "Tatsuniyoyin mutanen farko ne da ya rubuta su, waɗanda ake masa shiftar su safe da yamma."

6. Ka ce (da su): "Wanda Yake sane da asirin sammai da ƙasa Shi Ya saukar da shi. Lalle Shi Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafiran Larabawa suka riƙa ƙaryata Alƙur'ani har suna tuhumar Manzon Allah (ﷺ) da cewa shi ne ya ƙirƙiro shi da kansa, wasu mutane wai suka taimaka masa wajen ƙirƙirarsa. Suna nufin Yahudawa ne suka riƙa koya wa Manzon Allah (ﷺ) abin da yake faɗa da sunan Alƙur'ani. Allah ya tabbatar da cewa wannan maganar tasu zalunci ne kuma ƙarya ce

kawai suke faɗa. Alƙur'ani maganar Allah ce ba zai yiwu mutum ko aljan su iya kawo kamarsa ba, su ma masu ƙaryatawar sun san hakan.
Sannan Allah ya bayyana wata ƙarya ta biyu da suke yi dangane da Alƙur'ani, inda suke cewa, Alƙur'ani tatsuniyoyin mutanen farko ne da ƙarairayin da suka rubuta, shi kuma Annabi (ﷺ) ya riƙa juyar su a rubuce, ana karanta masa su safe da yamma.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya faɗa musu cewa, wanda ya saukar da Alƙur'ani shi ne masanin ɗaukacin abin da yake cikin sammai da ƙasa, don haka duk abin da yake cikin Alƙur'ani gaskiya ne babu ƙarya a ciki. Amma duk da haka sai da ya kwaɗaitar musu da tuba da neman gafarar Allah a kan ƙaryar da suke ƙirawa, ya tabbatar musu da cewa lalle shi mai karɓar tuba ne mai yawan gafara ne mai yawan jin ƙai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawa da manzanni mutane ne kamar sauran mutane, suna da buƙatu irin na mutane kamar ci da sha da hutu, sun fifita ne a kan sauran mutane da zaɓin da Allah ya yi musu ya ba su annabta, ya kuma hore su da kyawawan ɗabi'u da halaye na gari waɗanda suka fi sauran mutane da su.

2. Shiga kasuwanni domin saye da sayarwa ba laifi ne ba, kuma ba ya tauye darajar mumini.

3. Tufka-da-warwarar kafirai wajen siffanta Manzon Allah (ﷺ) wani dalili ne da ke nuna jahilcinsu da ƙaryarsu.

4. Gaskiya ɗaya ce, duk wanda ya bar ta to ya ɓace ba zai taɓa samun wata hanyar shiriya ba har sai ya dawo kan gaskiya.

Suratul Furƙan (7-9)
وَقَالُواْ مَالِ هَٰذَا ٱلرَّسُولِ يَأۡكُلُ ٱلطَّعَامَ وَيَمۡشِي فِي ٱلۡأَسۡوَاقِۖ لَوۡلَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مَلَكٞ فَيَكُونَ مَعَهُۥ نَذِيرًا ٧ أَوۡ يُلۡقَىٰٓ إِلَيۡهِ كَنزٌ أَوۡ تَكُونُ لَهُۥ
جَنَّةٞ يَأۡكُلُ مِنۡهَاۚ وَقَالَ ٱلظَّٰلِمُونَ إِن تَتَّبِعُونَ إِلَّا رَجُلٗا مَّسۡحُورًا ٨ ٱنظُرۡ كَيۡفَ ضَرَبُواْ لَكَ ٱلۡأَمۡثَالَ فَضَلُّواْ فَلَا يَسۡتَطِيعُونَ سَبِيلٗا ٩

7. Suka kuma ce: "Me ya sa wannan Manzo yake cin abinci kuma yake tafiya cikin kasuwanni? Me ya hana a saukar masa da mala'ika, sai ya zama mai gargaɗi tare da shi?

8. Ko a jefo masa wata taskar dukiya ko ya zama yana da wani lambu wanda daga gare shi zai riƙa ci?" Sai azzalumai suka ce "Ba wanda kuke bi sai wani mutum wanda aka yi wa sihiri!"

9. To ka dubi yadda suka riƙa buga maka misali, sai suka ɓata, don haka ba za su iya bin hanyar shiriya ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wautar kafirai a fili yayin da suka kawo wasu siffofi biyar waɗanda suke ganin wai su suka hana su yarda Annabi Muhammadu (ﷺ) Manzon Allah ne, waɗannan siffofi kuwa su ne:
Na ɗaya, sun ce me ya sa yana Manzo amma kuma yake cin abinci? Watau dai suna ganin su da shi babu bambanci, domin su ma suna cin abinci suna shan abin sha, shi ma yana ci yana sha.
Na biyu, yana fita kasuwa neman abinci. Watau idan haka yake to da me ya fi su kenan?
Na uku, me ya hana a saukar masa da mala'ika wanda za su riƙa fita wa'azi tare, idan ya faɗi magana ya gaskata shi, ya kuma mayar da martani ga duk wanda ya nemi ya saɓa masa?

Na huɗu, suka ce kuma me ya hana a saukar masa wata taska daga sama wadda za ta ishe shi duk buƙatunsa na yau da kullum, ba sai ya tafi cin kasuwa ba?
Na biyar, suka ce kuma me ya hana ya zama yana da wani lambu wanda zai riƙa cin 'ya'yan itatuwansa da shuke-shukensa, ba sai ya tafi nema a kasuwa ba?
Sai kuma suka ce wa muminai da suka yi imani da manzancin Annabi (ﷺ) wai ba Manzo suke bi ba, kawai dai suna bin wani sihirtaccen mutum ne wanda ya rasa hankalinsa a sanadiyyar sihiri da aka yi masa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya duba ya kuma yi mamakin yadda waɗannan kafirai suke ta siffanta shi da siffofi daban-daban, wani lokaci su ce masa mai sihiri wani lokaci kuma su ce mawaƙi ko su ce boka ko mai taɓin hankali. Saboda haka suka ɓata suka kasa gane hanyar shiriya, suka kuma kasa samun hanyar da za su soki gaskiyar Manzo (ﷺ) da amanarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Da Allah ya ga dama da ya ba wa Manzonsa (ﷺ) arzikin duniya da ya fi na kowa, to amma ita duniya ba a bakin komai take a wurin Allah ba, don haka yana bai wa masoyansa da manzanninsa gwargwadon yadda ya dace da hikimarsa.

2. Ƙaryata ranar alƙiyama abu ne da ke jawo kowane irin kafirci da rashin kunya ga Allah da annabawansa da ƙaryata gaskiya.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai haɗa wa kafirai azaba hawa-hawa a wutar Jahannama; za su fara firgita da cika da tsoro tun gabanin a jefa su a cikinta yayin da za su jiyo gurnaninta da gunjinta, sannan kuma a jefa su a cikinta a wani wuri mai ƙuncin gaske; ga cunkoso na yawansu, ga shi kuma an haɗa hannayensu da wuyayensu an ɗaure da sarƙoƙi, sannan kuma ba za su taɓa jin magana mai daɗi ba.

4. Babu wauta kamar ta wanda zai fifita kafirci a kan imani, domin wannan yana nufin fifita azaba madawwamiya a kan ni'ima dawwamammiya.

Suratul Furƙan (10-16)
تَبَارَكَ ٱلَّذِىٓ إِن شَآءَ جَعَلَ لَكَ خَيۡرًا مِّن ذَٰلِكَ جَنَّٰتٖ تَجۡرِى مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ وَيَجۡعَل لَّكَ قُصُورَۢا ﴿١٠﴾ بَلۡ كَذَّبُواْ بِٱلسَّاعَةِۖ وَأَعۡتَدۡنَا لِمَن كَذَّبَ بِٱلسَّاعَةِ سَعِيرًا ﴿١١﴾ إِذَا رَأَتۡهُم مِّن مَّكَانِۭ بَعِيدٖ سَمِعُواْ لَهَا تَغَيُّظٗا وَزَفِيرٗا ﴿١٢﴾ وَإِذَآ أُلۡقُواْ مِنۡهَا مَكَانٗا ضَيِّقٗا مُّقَرَّنِينَ دَعَوۡاْ هُنَالِكَ ثُبُورٗا ﴿١٣﴾ لَّا تَدۡعُواْ ٱلۡيَوۡمَ ثُبُورٗا وَٰحِدٗا وَٱدۡعُواْ ثُبُورٗا كَثِيرٗا ﴿١٤﴾ قُلۡ أَذَٰلِكَ خَيۡرٌ أَمۡ جَنَّةُ ٱلۡخُلۡدِ ٱلَّتِى وُعِدَ ٱلۡمُتَّقُونَۚ كَانَتۡ لَهُمۡ جَزَآءٗ وَمَصِيرٗا ﴿١٥﴾ لَّهُمۡ فِيهَا مَا يَشَآءُونَ خَٰلِدِينَۚ كَانَ عَلَىٰ رَبِّكَ وَعۡدٗا مَّسۡـُٔولٗا ﴿١٦﴾

10. Albarkatun (Allah) sun yawaita, wanda idan Ya ga dama sai Ya sanya maka alheri fiye da waɗannan: (su ne) gonakai waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, Ya kuma sanya maka maka-makan gidaje.

11. Ba haka ba ne, sun dai ƙaryata tashin alƙiyama ne; Mun kuwa tanadi (wutar) Sa'ira ga wanda ya ƙaryata tashin alƙiyama.

12. Idan (wutar) ta hango su daga wuri mai nisa sai su ji tafarfasa da gurnaninta.

13. Idan kuwa aka jefa su cikinta a wani wuri ƙuntatacce nata, suna ƙuƙunce, sai su riƙa kiran hallaka a can.

14. (Sai a ce da su): "A yau kada ku kirawo hallaka ɗaya kawai, ku kirawo hallaka da yawa!"

15. Ka ce (da su): “Yanzu wannan ne ya fi alheri, ko kuwa Aljannar dawwama wadda aka yi wa masu taƙawa alƙawarinta, ta zama sakamako da makoma a gare su?”

16. Suna da duk abin da suka ga dama a cikinta, masu madawwama ne. (Wannan kuma) ya kasance alƙawari ne abin tambaya a kan Ubangijnka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa cewa, duk waɗannan abubuwa da kafirai suke cewa me ya sa Allah bai yi masa su ba, to su sani cewa, alhairan Allah da albarkatunsa suna da yawa, idan ya ga dama sai ya ba shi abubuwan da suka fi waɗannan alheri, watau a nan duniya sai ya ba shi gonaki waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, kuma ya ba shi maka-makan gidaje waɗanda dukiyarsu ba za ta iya saya musu kamarsu ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin da ya jawo suke ƙaryata manzancin Annabi (ﷺ) suke irin waɗancan miyagun maganganu, watau don sun ƙaryata tashin alƙiyama, wannan shi ne abin da ya hana su binciken gaskiya da dalilinta don su bi ta. Allah ya tabbatar musu da cewa ya tanadar wa duk wanda ya ƙaryata ranar alƙiyama azabar wuta mai ruruwa.
Sai kuma ya bayyana yanayin wutar da take jiran su da cewa, idan ta hango su ana koro su zuwa gare ta daga wuri mai nisa, sai su riƙa jin tafarfasarta da gurnaninta. Idan aka jefa su cikin wutar Jahannama a wani wuri ƙuntatacce a cikinta an ɗaɗɗaure hannayensu a wuyayensu da sarƙoƙi, sai su riƙa kirawo wa kansu halaka suna tsammanin ko sa kuɓuta. Sai a faɗa musu cewa su daina ma kiran hallaka guda ɗaya, su ma kirawo halaka da yawa, wannan ba zai amfane su da komai ba, domin ba za a saurari kiransu ba, za su yi ta zama ne cikin matsananciyar azaba har abada.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya faɗa musu cewa, yanzu wannan azabar da aka siffanta musu ita ce ta fi alheri ko kuma Aljannar dawwama wadda ni’imominta ba sa yankewa har abada? Ita ce wadda ya yi wa bayinsa muminai masu taƙawa alƙawarinta, don ta zama sakamako da makoma gare su a ranar alƙiyama?
Ya bayyana cewa, za su sami duk abin da suka buƙata na ni’ima a cikin gidan Aljanna, wannan alƙawari ne Allah ya yi wa masu taƙawa da za su tambaye shi don ya cika musu shi domin shi ba ya saɓa alƙawari.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan waɗanda aka bauta wa ba Allah ba za su nesanta kansu daga masu bautarsu ranar alƙiyama.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai azabtar da waɗanda aka bauta musu ba da umarninsu ba kuma ba da yardarsu ba.

3. Shirka zalunci ne babba, don haka mai yin ta ya cancanci azaba mai girma matuƙar ya mutu bai tuba ba.

Suratul Furƙan (17-19)
وَيَوۡمَ يَحۡشُرُهُمۡ وَمَا يَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ فَيَقُولُ ءَأَنتُمۡ أَضۡلَلۡتُمۡ عِبَادِي هَٰٓؤُلَآءِ أَمۡ هُمۡ ضَلُّواْ ٱلسَّبِيلَ ١٧ قَالُواْ سُبۡحَٰنَكَ مَا كَانَ يَنۢبَغِي لَنَآ أَن نَّتَّخِذَ مِن دُونِكَ مِنۡ أَوۡلِيَآءَ وَلَٰكِن مَّتَّعۡتَهُمۡ وَءَابَآءَهُمۡ حَتَّىٰ نَسُواْ ٱلذِّكۡرَ وَكَانُواْ قَوۡمۢا بُورَۢا ١٨ فَقَدۡ كَذَّبُوكُم بِمَا تَقُولُونَ فَمَا تَسۡتَطِيعُونَ صَرۡفٗا وَلَا نَصۡرٗاۚ وَمَن يَظۡلِم مِّنكُمۡ نُذِقۡهُ عَذَابٗا كَبِيرٗا ١٩

17. (Ka tuna) kuma ranar da zai tara su da abin da suke bauta wa ba Allah ba, sai Ya ce (da su): “Shin yanzu ku ne kuka ɓatar da bayina waɗannan, ko kuwa su ne suka ɓace wa hanya don kansu?”

18. Suka ce: “Tsarki ya tabbata gare Ka, bai zamanto ya dace da mu ba mu riƙi wasu majiɓinta ba Kai ba, sai dai kuma Ka jiyar da su daɗi ne tare da iyayensu har suka manta tuna Ka, suka kuwa kasance mutane hallakakku.”

19. To haƙiƙa sun ƙaryata ku game da abin da kuke faɗa, to ba za ku samu wata makauta ba, ko kuma wani taimako. Duk wanda kuma ya yi zalunci daga cikinku za Mu ɗanɗana masa azaba mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai masu bautar wasu ba Allah ba, kamar masu bautar mala’iku ko masu bautar annabawa, kamar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ko masu bautar wasu salihan bayi, ya tuna musu ranar da zai tattara su baki ɗaya sai ya tambayi ababen bautar cewa, shin su ne suka ɓatar da waɗannan bayin nasa, suka umarce su da su bauta musu? Ko kuma su bayin ne suka ɓace don kansu?
Sai waɗannan ababen bauta su kare kansu a gaban Allah, su tabbatar masa da cewa tsarki ya tabbata a gare shi da a ce yana da wani abokin tarayya, kuma bai dace gare su ba su riƙi wasu masoya da za su jiɓince su ba Allah ba. Don haka ta yaya za su kirawo wasu bayinsa su umarce su su bauta musu? Suka bayyana abin da ya jawo waɗannan suka kafirce da cewa, Allah ne ya hore musu abubuwan jin daɗi na duniya mai yawa su da iyayensu, domin su gode masa su kuma bauta masa shi kaɗai, to amma sai ba su yi haka ba, wannan ni’imar ta zamar musu talala har suka manta da ambaton Allah, suka ci gaba da bautar wasu ba shi ba, suka kuwa kasance mutane halakakku.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai cewa haƙiƙa waɗanda suka bauta wa ba Allah ba ga shi sun ƙaryata su a kan da’awarsu ta cewa su ne suka umarce su da bautar su, kuma ma har za su cece su a wurin Allah. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa a ranar ba za su iya kare kansu daga azabarsa ba, ba kuma za su iya taimakon kawunansu ba. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa duk wanda ya aikata zalunci daga cikinsu ta hanyar shirka, to zai ɗanɗana masa azaba mai girma kamar dai irin wadda ambatonta ya gabata.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan annabawan da Allah ya aiko mutane ne waɗanda suke ci suke sha suke shiga kasuwanni don biyan buƙatarsu ta rayuwa.

2. Duniya gida ne na jarraba, don haka yake buƙatar haƙuri da juriya wajen biyayyar Allah da guje wa saɓa masa, da haƙuri a kan duk wata ƙaddara marar daɗi.

3. Falalar haƙuri da muhimmancinsa a rayuwa.

Suratul Furƙan (20)
وَمَآ أَرۡسَلۡنَا قَبۡلَكَ مِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ إِلَّآ إِنَّهُمۡ لَيَأۡكُلُونَ ٱلطَّعَامَ وَيَمۡشُونَ فِي ٱلۡأَسۡوَاقِۗ وَجَعَلۡنَا بَعۡضَكُمۡ لِبَعۡضٖ فِتۡنَةً أَتَصۡبِرُونَۗ وَكَانَ رَبُّكَ بَصِيرٗا ٢٠

20. Kuma ba Mu aiko manzanni ba gabaninka sai cewa lalle suna cin abinci kuma suna tafiya cikin kasuwanni. Mun kuwa sanya wasunku su zama fitina ga wasu. Shin za ku yi haƙuri? Ubangijinka kuwa Ya kasance Mai gani ne.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da martani ga kafirai waɗanda suke ganin bai dace a ce manzo yana cin abinci yana zuwa kasuwanni saye da sayarwa ba, da cewa ai babu wani manzo da ya

aiko gabanin Manzo (ﷺ) face shi mutum ne mai cin abinci kuma yana tafiya kasuwanni, don haka Manzon Allah (ﷺ) bai zama daban ba a nan. Sai kuma ya bayyana cewa ya sanya wasu mutane su zama fitina ga wasu, don haka manzanni sukan zama fitina ga masu ƙaryata su, masu ɗa'a sukan zama fitina a wurin mai saƃo, masu wadata kuma sukan zama fitina ga marasa wadata. Abin nema ga mutane dai shi ne su yi haƙuri a kan duk wata jarraba da Allah zai yi wa bawansa, sai ya yi masa sakayya idan ya yi haƙuri. Allah ya tabbatar da cewa yana ganin kowa; masu haƙuri da waɗanda ba sa haƙuri; masu biyayya da waɗanda ba sa biyayya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin tsananin taurin kan kafirai da girman kansu.

2. Kafirai za su ga mala'iku amma ganin da ba zai yi musu daɗi ba; za su gan su lokacin da za su zo ɗaukar ransu yayin mutuwarsu; za su gan su kuma lokacin da Munkarun da Nakiru za su zo musu a ƙabari domin yi musu tambayoyi; hakanan za su gan su lokacin da za su kora su zuwa Jahannama sannan su danƙa su a hannun mala'iku masu tsaron Jahannama waɗanda za su ci gaba da gana musu azaba.

3. Duk wani aikin ƙwarai na kafiri ba zai amfane shi ba a ranar alƙiyama saboda bai yi imani da Allah da Manzonsa ba. Sharaɗin amfana da aikin ƙwarai shi ne imani.

4. Za a gama hisabi a ranar alƙiyama gabanin lokacin Azahar, domin 'yan Aljanna za su shiga gidajensu na Aljanna har su riski lokacin ƙailula a cikinta. Hakanan 'yan wuta su ma za su riski wannan lokacin a cikin wuta.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa mushirikai cewa gidajen muminai 'yan Aljanna sun fi gidajensu da suke alfahari da su a nan duniya, domin abin da Allah ya tanada musu a can na hutu da jin daɗi ya fi nasu nesa ba kusa ba.

Suratul Furƙan (21-24)

*وَقَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡنَا ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَوۡ نَرَىٰ رَبَّنَاۗ لَقَدِ ٱسۡتَكۡبَرُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ وَعَتَوۡ عُتُوّٗا كَبِيرٗا ٢١ يَوۡمَ يَرَوۡنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ لَا بُشۡرَىٰ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُجۡرِمِينَ وَيَقُولُونَ حِجۡرٗا مَّحۡجُورٗا ٢٢ وَقَدِمۡنَآ إِلَىٰ مَا عَمِلُواْ مِنۡ عَمَلٖ فَجَعَلۡنَٰهُ هَبَآءٗ مَّنثُورًا ٢٣ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِ يَوۡمَئِذٍ خَيۡرٞ مُّسۡتَقَرّٗا وَأَحۡسَنُ مَقِيلٗا ٢٤

21. Waɗanda kuma ba sa tsammanin haɗuwa da Mu suka ce: "Me ya hana a saukar mana da mala'iku ko kuma mu ga Ubangijinmu?" Haƙiƙa lalle sun yi girman kai don (suna) ji da kawunansu, suka kuma yi tsaurin kai babba ƙwarai da gaske.

22. Ranar da za su ga mala'iku a wannan ranar babu wani farin ciki ga masu laifi, za kuma su riƙa cewa: "(Albishir daga Allah) haramun ne abin haramtawa ne (a gare su)"

23. Muka kuma gabato zuwa ga duk wani aiki da suka yi, sai Muka mai da shi ƙura abar ɗaiɗaitawa.

24. 'Yan Aljanna a wannan ranar su suka fi kyakkyawan mazauni kuma suka fi kyawon wurin barcin ƙailula.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kafirai waɗanda ba sa fatan haɗuwa da shi kuma ba sa jin tsoron azabarsa suna izgili na cewa me ya sa Allah bai saukar musu da mala'iku ba waɗanda za su tabbatar musu cewa Annabi mai gaskiya ne game da da'awar manzanci da ya yi, ko kuma

me ya hana su ga Allah da kansa ido-da-ido shi ya tabbatar musu da haka da kansa? Allah ya bayyana cewa, lalle waɗannan mutane girman kansu ya kai matuƙa, ya hana su yin imani da har suke nuna tsageranci ga mahaliccinsu suke ganin cewa wai su ne za su zabi hanyar da Allah zai isar musu da saƙonsa; idan kuwa bai bi wannan hanyar ba to ba za su yi imani ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa ranar da za su ga mala'iku, watau ranar mutuwarsu ko a cikin ƙaburburansu da ranar da za a kora su domin yi musu hisabi, to a ranar babu sauran wani farin ciki a tare da su. A ranar mala'iku za su riƙa gaya musu cewa babu wani albishir daga Allah sai na matsananciyar azaba.
Sannan Allah ya bayyana cewa duk wani kyakkyawan aiki da kafirai suka yi a duniya wanda suke sa ran za su amfana da shi ranar alƙiyama, ya mayar da shi ƙura abar ɗaiɗaitawa, saboda kafircinsu, domin sharaɗin amfanuwa da kyawawan ayyuka shi ne yin imani da Allah da Manzonsa.
Sai kuma ya bayyana sakamakon muminai a ranar alƙiyama da cewa, su ne 'yan Aljanna waɗanda za su fi kowa kyakkyawar matabbata da mafi kyan wurin barcin ƙailula domin samun hutu, saboda sun yi imani da Allah da Manzonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ranar alƙiyama rana ce da ke cike da abubuwan mamaki na ban tsoro da tashin hankali.

2. Ranar alƙiyama rana ce mawuyaciya ga kafirai amma mai sauƙi ce ga muminai.

3. Hatsarin abota da lalataccen aboki wanda ba zai nuna wa mutum hanyar ƙwarai ba sai dai ya yi ta yi masa ingiza mai kantu ruwa har ya kai shi ga hallaka ya baro.

4. Babu wata hanyar tsira sai tare da bin Annabi (ﷺ) da koyarwarsa.

Suratul Furƙan (25-29)
وَيَوْمَ تَشَقَّقُ ٱلسَّمَآءُ بِٱلْغَمَٰمِ وَنُزِّلَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ تَنزِيلًا ﴿٢٥﴾ ٱلْمُلْكُ يَوْمَئِذٍ ٱلْحَقُّ لِلرَّحْمَٰنِ ۚ وَكَانَ يَوْمًا عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ عَسِيرًا ﴿٢٦﴾ وَيَوْمَ يَعَضُّ ٱلظَّالِمُ عَلَىٰ يَدَيْهِ يَقُولُ يَٰلَيْتَنِى ٱتَّخَذْتُ مَعَ ٱلرَّسُولِ سَبِيلًا ﴿٢٧﴾ يَٰوَيْلَتَىٰ لَيْتَنِى لَمْ أَتَّخِذْ فُلَانًا خَلِيلًا ﴿٢٨﴾ لَّقَدْ أَضَلَّنِى عَنِ ٱلذِّكْرِ بَعْدَ إِذْ جَآءَنِى ۗ وَكَانَ ٱلشَّيْطَٰنُ لِلْإِنسَٰنِ خَذُولًا ﴿٢٩﴾

25. Kuma (ka tuna) ranar da sama za ta kekkece da girgije, kuma a saukar da mala'iku gungu-gungu.

26. Mulki tabbatacce a wannan ranar na (Allah) Mai rahama ne. Kuma ta kasance rana ce mawuyaciya ga kafurai.

27. (Ka tuna) kuma ranar da azzalumi zai riƙa cizon yatsunsa yana cewa: "Ina ma na bi hanya tare da Manzo!

28. "Kaicona ina ma da ban riƙi wane aboki ba!

29. "Haƙiƙa ya ɓatar da ni daga bin Alƙur'ani, bayan ya zo mini." Shaiɗan kuwa ya kasance mai taɓar da mutum ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tuna wa Manzonsa (ﷺ) ranar alƙiyama, ranar da sama za ta kekkece sai kawai a ga wani girgije fari kewaye da mala'iku masu yawa suna ta saukowa domin

gudanar da hisabi. Mulki tabbatacce na gaskiya a ranar na Allah ne mai rahama shi kaɗai, kuma rana ce mai tsananin wahala ga kafirai saɓanin muminai waɗanda za ta zo musu da sauƙi.
Allah ya bayyana halin kafiri a wannan rana, lokacin da zai riƙa nadama yana cizon ɗan yatsansa yana cewa ina ma da ya bi Manzon Allah ya karɓi gaskiyar da ya zo masa da ita bai ƙaryata shi ba, ya kama hanyar tsira tare da shi. A cikin tsananin nadama da ɓacin rai ya riƙa cewa kaiconsa, ina ma dai bai yi abota da wani kafiri ba wanda ya yi ta yi masa ingiza mai kantu ruwa. A ranar ya tabbatar da cewa wannan aboki nasa fa ya ɓatar da shi daga bin gaskiya bayan Manzon Allah ya zo masa da ita, ya hana shi yarda da Alƙur'ani da aiki da shi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mutum yana kan tafarkin abokinsa ne, don haka ɗayanku ya duba wanda zai yi abota da shi." [Abu Dawud #4833 da Tirmizi #2378 da Ahmad #8028].

An karɓo daga Abu Musa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Misalin abokin zama na ƙwarai da wanda ba na ƙwarai ba kamar mai ɗauke ne da turaren almiski da mai hura zugazugi; shi mai ɗauke da turaren almiski ko dai ya 'yam maka ko ka saya daga wajensa, ko kuma ka shaƙi ƙamshinsa. Amma mai hura zugazugi ko dai ya ƙona maka tufafinka ko ka shaƙi warinsa." [Bukhari #5534 da Muslim #2628].

Sai Allah ya tabbatar da cewa da man shi Shaiɗan ya kasance mai yawan taɓar da mutum ne ya kuma yi banza da shi lokacin da ya faɗa cikin wani bala'i.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin haɗarin ƙaurace wa Alƙur'ani.

2. Bayanin al'adar Allah cikin halittarsa cewa duk wani annabi sai da ya sanya masa abokan gaba daga cikin masu laifi, watau kafirai.

3. Karawa tsakanin ƙarya da gaskiya tana ƙara fito da gaskiya fili, ta kuma ba ta rinjaye a kan ƙarya. A lokacin ne kuma za a ga yadda Allah yake karrama masu gaskiya ya ƙaskanta maƙaryata maɓarnata.

Suratul Furƙan (30-31)
وَقَالَ ٱلرَّسُولُ يَٰرَبِّ إِنَّ قَوْمِى ٱتَّخَذُوا۟ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانَ مَهْجُورًا ﴿٣٠﴾ وَكَذَٰلِكَ جَعَلْنَا لِكُلِّ نَبِىٍّ عَدُوًّا مِّنَ ٱلْمُجْرِمِينَ ۗ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ هَادِيًا وَنَصِيرًا ﴿٣١﴾

30. Manzo kuma ya ce: "Ya Ubangijina, lalle mutanena sun riƙi wannan Alƙur'ani abin ƙaurace wa."

31. Kamar haka Muka sanya wa kowanne annabi abokan gaba daga masu laifi, kuma Ubangijinka Ya ishe ka Mai shiryarwa Mai taimako.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda Manzon Allah (ﷺ) yake ta kokawa game da halayyar kafirai waɗanda suke bijire wa Alƙur'ani da ya zo yana karanta musu suka riƙa yi masa izgili da ta'annuti iri-iri, duk da cewa wajibi ne a kansu su yi imani da shi su miƙa wuya a gare shi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) ya sanar da shi cewa irin wannan cin zarafi da yake fuskanta daga kafirai shi ne abin da sauran annabawa da suka gabace shi suka fuskanta daga kafiran zamaninsu, amma suka yi haƙuri, daga ƙarshe Allah ya ɗora su a kan maƙiyansu. Don haka shi ma ya yi haƙuri, Ubangijinsa ya ishe shi mai shiryarwa zuwa gaskiya kuma mai ba shi nasara a kan maƙiyansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin ta'annutin kafirai wajen sukan Alƙur'ani da neman abin da za su fake da shi komai ƙanƙantarsa don su ƙaryata Alƙur'ani da shi.

2. Bayanin saukar da Alƙur'ani kaɗan-kaɗan da nuna wasu daga cikin hikimomin yin hakan kamar:
• Tabbatar da zuciyar Manzon Allah (ﷺ) da kwantar masa da hankali duk lokacin da wata damuwa ta faru gare shi.
• Domin sauƙaƙe kiyaye shi da haddace shi da fahimtar sa.
• Da a ce ya sauka gaba ɗaya to da an saukar da shari'a da hukunce-hukunce gaba ɗaya a lokaci guda wanda yin haka wahalarwa ce ga al'umma da tsanantawa.
• Idan Annabi (ﷺ) zai riƙa ganin Mala'ika Jibrilu yana saukowa gare shi lokaci bayan lokaci, hakan zai ƙara masa ƙarfin zuciya da juriya a kan isar da saƙon Allah.
• An saukar da hukunce-hukunce ne gwargwadon tambayoyin sahabbai da abubuwan da suka riƙa faruwa yau da gobe; wannan kuwa wani abu ne da zai ƙara musu fahimtar addininsu.
• Ya sauka kaɗan-kaɗan kuma domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci kafiran Larabawa su zo da wani abu kwatankwacinsa amma suka kasa, to ina kuma da a ce a dunƙule gaba ɗaya Allah ya saukar da shi, ta yaya za su iya kwaikwayon sa?
• Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wasu hukunce-hukuncensa gwargwadon buƙatar Musulmi a lokacin ko kuma saboda wata hikima da shi ya san ta, daga baya ya canza wasu hukunce-hukuncen da waɗanda suka fi na farko ko daidai da su, saboda wasu dalilai. Da a ce a dunƙule a karo ɗaya ya saukar da shi to da hakan bai samu ba.

Suratul Furƙan (32-34)
وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡلَا نُزِّلَ عَلَيۡهِ ٱلۡقُرۡءَانُ جُمۡلَةٗ وَٰحِدَةٗۚ كَذَٰلِكَ لِنُثَبِّتَ بِهِۦ فُؤَادَكَۖ وَرَتَّلۡنَٰهُ تَرۡتِيلٗا ٣٢ وَلَا يَأۡتُونَكَ بِمَثَلٍ إِلَّا جِئۡنَٰكَ بِٱلۡحَقِّ وَأَحۡسَنَ تَفۡسِيرًا ٣٣ ٱلَّذِينَ يُحۡشَرُونَ عَلَىٰ وُجُوهِهِمۡ إِلَىٰ جَهَنَّمَ أُوْلَٰٓئِكَ شَرّٞ مَّكَانٗا وَأَضَلُّ سَبِيلٗا ٣٤

32. Waɗanda kuma suka kafirta suka ce: "Me ya hana a saukar masa da Alƙur'ani gaba ɗaya, a lokaci guda?" Kamar haka ne (Muke saukar da shi kaɗan-kaɗan) don Mu tabbatar da zuciyarka da shi, Muka kuma karantar (da kai) shi daki-daki.

33. Kuma ba za su zo maka da wani misali ba (na ƙalu-bale) sai Mun zo maka da gaskiya, kuma da mafi kyan bayani.

34. Waɗanda za a tashe su zuwa wutar Jahannama a kan fuskokinsu, waɗannan su suka fi mummunan matsayi kuma mafiya ɓatacciyar hanya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani salo daban na ƙaryata Alƙur'ani da kafirai suka fito wa da Manzon Allah (ﷺ) shi, yayin da suka nuna masa cewa da Alƙur'ani gaskiya ne daga Allah yake to da shi ma an saukar da shi gaba ɗaya kamar yadda aka saukar wa Annabi Musa Attaura da yadda aka saukar wa Annabi Isa Injila. To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa ya saukar da Alƙur'ani ne kaɗan-kaɗan domin ya tabbatar da zuciyar Annabi (ﷺ) ya ƙara mata nutsuwa, kuma ya yi haka ne don a sami sauƙin fahimtar sa da haddace shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa babu sanda kafirai za su zo masa da wani misali wanda za su buƙaci amsa daga gare shi face sai Allah ya zo masa da tabbatacciyar amsa ta gaskiya da kuma bayani mafi kyau mai gamsarwa.

Sai kuma ya bayyana mummunan sakamakon masu ƙaryata Alƙur’ani da gaskiya a ranar alƙiyama, da cewa su ne waɗanda za a kora su zuwa wutar Jahannama ana jan su a kan fuskokinsu, waɗannan su ne suka fi mummunan matsayi, domin mazauninsu ita ce wutar Jahannama, kuma su ne mafiya nesanta daga hanyar gaskiya, domin hanyar kafirci da ɓata ita ce hanyarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirce wa Allah da ƙaryata ayoyinsa su ne suka jawo Allah ya hallaka al’ummun da suka gabata.

2. Duk wanda ya ƙaryata manzo ɗaya, to ya ƙaryata sauran manzanni ne baki ɗaya.

3. Rashin imanin kafiran Kuraishawa da tashin alƙiyama shi ne ya sanya su ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) .

Suratul Furƙan (35-40)

وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ وَجَعَلۡنَا مَعَهُۥٓ أَخَاهُ هَٰرُونَ وَزِيرٗا ٣٥ فَقُلۡنَا ٱذۡهَبَآ إِلَى ٱلۡقَوۡمِ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَدَمَّرۡنَٰهُمۡ تَدۡمِيرٗا ٣٦ وَقَوۡمَ نُوحٖ لَّمَّا كَذَّبُواْ ٱلرُّسُلَ أَغۡرَقۡنَٰهُمۡ وَجَعَلۡنَٰهُمۡ لِلنَّاسِ ءَايَةٗۖ وَأَعۡتَدۡنَا لِلظَّٰلِمِينَ عَذَابًا أَلِيمٗا ٣٧ وَعَادٗا وَثَمُودَاْ وَأَصۡحَٰبَ ٱلرَّسِّ وَقُرُونَۢا بَيۡنَ ذَٰلِكَ كَثِيرٗا ٣٨ وَكُلّٗا ضَرَبۡنَا لَهُ ٱلۡأَمۡثَالَۖ وَكُلّٗا تَبَّرۡنَا تَتۡبِيرٗا ٣٩ وَلَقَدۡ أَتَوۡاْ عَلَى ٱلۡقَرۡيَةِ ٱلَّتِيٓ أُمۡطِرَتۡ مَطَرَ ٱلسَّوۡءِۚ أَفَلَمۡ يَكُونُواْ يَرَوۡنَهَاۚ بَلۡ كَانُواْ لَا يَرۡجُونَ نُشُورٗا ٤٠

35. Haƙiƙa kuma Mun bai wa Musa Littafi muka kuma sanya ɗan’uwansa Haruna tare da shi a matsayin Waziri.

36. Sai Muka ce: “Ku tafi zuwa ga mutanen da suka ƙaryata ayoyinmu, sai Muka hallaka su hallakarwa mai tsanani!”

37. Mutanen Nuhu kuma lokacin da suka ƙaryata manzanni sai Muka nutsar da su, Muka kuma sanya su wa’azi ga mutane, kuma Muka tanadi azaba mai raɗaɗi ga azzalumai.

38. Kuma (Muka hallakar da) Adawa da Samudawa da kuma mutanen (rijiyar) Rassu, da kuma wasu al’ummu masu yawa tsakanin hakan.

39. Kowannensu kuwa Mun ba shi misalai; kuma kowannensu Mun hallaka shi mummunar hallakawa.

40. Haƙiƙa kuma (su mutanen Makka) sun bi ta alƙaryar nan wadda aka yi wa ruwan azaba. Shin ba su kasance suna ganin ta ba ne? Ba haka ba ne, sun dai kasance ne ba sa tsammanin tashin alƙiyama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwantar da hankalin Manzonsa tare da lallashin sa game da ƙaryatawar da kafirai suke yi masa da cewa, annabawa da dama da suka gabace shi sun fuskanci ƙalubale daga mutanensu amma daga ƙarshe Allah ya ba su nasara a kansu. Allah ya tunatar masa da Annabi Musa wanda ya ba shi littafin Attaura ya kuma haɗa shi da ɗan’uwansa Annabi Haruna don ya zame masa Waziri da zai taimaka masa isar da saƙo zuwa ga Fir’auna da mutanensa. Allah ya umarce su da su fuskanci Fir’auna da mutanensa waɗanda suka ƙaryata ayoyin Allah masu nuna Kaɗaitakar Allah da Rububiyyarsa. Suka kuwa same su suka kirawo su zuwa ga Tauhidi, to amma sai suka ƙaryata su, Allah kuwa a ƙarshe ya yi musu mummunar halakarwa a kogi.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata masa labarin mutanen Annabi Nuhu waɗanda suka ƙaryata manzanni ta hanyar ƙaryata Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai Allah ya halakar da su baki ɗaya a ruwan Ɗufana, ya kuma sanya hallakarsu ta zama wata babbar aya ga mutane da ke nuna Kudurar Allah wajen tunɓuke azzalumai da nuna musu ƙarshensu. Allah kuma ya bayyana cewa ya tanadar wa azzalumai azaba mai raɗaɗi a ranar alƙiyama tana nan tana jiran su.
Sannan kuma ya bayyana masa cewa ya hallakar da Adawa mutanen Annabi Hudu da Samudawa mutanen Annabi Salihu, ya kuma hallakar da mutanen rijiyar Rassu da kuma wasu al'ummu masu yawa a tsakanin waɗancan al'ummu guda uku. Allah kuma ya yi masa bayanin yadda ya hallakar da al'ummun da suka gabace su da dalilan da suka jawo ya hallaka su domin su wa'azantu; dukkansu kuma ya yi musu mummunar hallakarwa ne saboda kafircinsu da tsaurin kansu.
Allah kuma ya ambata wa Manzonsa cewa mutanensa Larabawa masu ƙaryata shi suna bi ta alƙaryar mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda aka yi wa ruwan ƙananan duwatsu saboda mummunar alfasha da suka aikata da neman maza. Larabawa a lokacin tafiye-tafiyensu zuwa ƙasar Sham suna bi ta wannan alƙarya mai cike da ababen wa'azantuwa, to shin sun makance ba sa ganin wannan alƙaryar ne? A'a, kawai dai ba sa tsammanin cewa akwai ranar da za a tashe su bayan sun mutu a yi musu hisabi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yi wa masu gaskiya izgili ɗabi'a ce ta kafirai tun da can fil-azal.

2. Izgilin da kafiran Kuraishawa suka riƙa yi wa Manzon Allah na nuna rashin cancantar a ba shi manzanci shaƙiyanci ne kawai da tsabar rashin kunya, domin kuwa daga cikinsu ba wanda bai san girman matsayin Manzon Allah (ﷺ) da cikar hankalinsa da iliminsa da jarumtarsa da asalinsa ba tun ma gabanin a ba shi manzanci. Tun tasowarsa suna yaba wa hankalinsa da gaskiyarsa da riƙon amanarsa da kame kansa, ɗabi'un da babu wanda ya kama ƙafarsa a cikinsu. Sai kuma daga baya su ne za su zo da batun cewa wai bai cancanci manzanci ba har suna yi masa izgili da wannan?

3. Saboda jirkita gaskiya ta kafirai har ta kai suna ganin Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta, shi ne ɓata, shirka da suke kai kuwa ita ce shiriya, don haka har suna yi wa juna wasiyya da su yi ta haƙuri da juriya wajen riƙe abin da suke kai na kafirci gam-gam.

4. Haɗarin bin son zuciya. Duk wanda ya saki shiriyar Allah yana sane don kawai daɗaɗa wa zuciyarsa, to wannan ya mayar da zuciyarsa abin bautarsa.

5. Idan mutum ya jahilci gaskiya ko ruɗani ya toshe masa fahimtarsa, wannan ana sa ran wata rana ya gane gaskiya ya shiriya. To amma wanda ya mayar da son zuciya abin bautarsa to wannan abu ne mai matuƙar wahala ya dawo ya shiriya ya bi gaskiya.

6. Dabbobi sun fi kafirai a wurin Allah, domin dabba duk da cewa Allah bai ba ta hankali kamar na ɗan'adam ba, to amma takan nemi abin da zai amfane ta, takan kuma nisanci abin da zai cutar da ita. Amma shi kafiri duk da hankali da Allah ya ba shi sai ya zaɓi abin da zai cutar da shi duniya da lahira ya ƙi abin da zai amfane shi duniya da lahira.

Suratul Furƙan (41-44)

وَإِذَا رَأَوْكَ إِن يَتَّخِذُونَكَ إِلَّا هُزُوًا أَهَٰذَا ٱلَّذِى بَعَثَ ٱللَّهُ رَسُولًا ﴿٤١﴾ إِن كَادَ لَيُضِلُّنَا عَنْ ءَالِهَتِنَا لَوْلَآ أَن صَبَرْنَا عَلَيْهَا ۚ وَسَوْفَ يَعْلَمُونَ حِينَ يَرَوْنَ ٱلْعَذَابَ مَنْ أَضَلُّ سَبِيلًا ﴿٤٢﴾ أَرَءَيْتَ مَنِ ٱتَّخَذَ إِلَٰهَهُۥ هَوَىٰهُ أَفَأَنتَ تَكُونُ عَلَيْهِ وَكِيلًا ﴿٤٣﴾ أَمْ تَحْسَبُ أَنَّ أَكْثَرَهُمْ يَسْمَعُونَ أَوْ يَعْقِلُونَ ۚ إِنْ هُمْ إِلَّا كَٱلْأَنْعَٰمِ بَلْ هُمْ أَضَلُّ سَبِيلًا ﴿٤٤﴾

41. Idan kuma suka gan ka ba sa riƙon ka sai abin yi wa izgili, (suna cewa): “Yanzu wannan ne wanda Allah ya aiko Manzo?

42. “Lalle saura ƙiris ya ɓatar da mu daga ababen bautarmu, ba don mun yi haƙuri a kansu ba.” Ba da daɗewa ba kuwa za su san wanda ya fi ɓatan hanya yayin da za su ga azaba.

43. Shin ka ga wanda ya mayar da son zuciyarsa (shi ne) abin bautarsa, to yanzu kai za ka zama mai kiyaye shi (daga bin son zuciyarsa)?

44. Ko kuwa kana tsammanin cewa yawancinsu suna ji ne (na fahimta) ko suna hankalta? Ai su ba wasu ba ne illa kamar dabbobi; a’a su ne ma suka fi (dabbobi) ɓace hanya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin yadda kafirai suka riƙa yi wa Manzon Allah izgili da rashin kunya duk sanda suka haɗu da shi. A cikin izgilinsu suna ce masa; “Yanzu wannan shi ne Manzon da Allah ya aiko mana?” Watau suna ganin bai isa a ba shi manzanci ba domin a lissafinsu shi ba kowa ba ne, ba shi da wani babban matsayin da zai cancanci manzanci a dalilinsa. Wannan yana nuna tsantsar jahilcinsu da rashin sanin wane ne Allah. Don haka sai suke cewa cikin izgili da tsokana cewa wai saura ƙiris ya ɓatar da su domin zai kautar da su daga bautar allolinsu ba don sun yi haƙuri da juriya a kan haka ba, da hujjojinsa sun sanya su sun bi shi sun bar gumakansu. Sai Allah ya bayyana musu cewa yayin da za su ga azaba a ƙaburburansu ko a ranar alƙiyama ai za su gane wanda ya fi ɓace hanya tsakanin su da shi, za su san wane ne ɓatacce a cikinsu, shi ko su.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa waɗannan mutane son zuciya kawai suke bi ba hujja ba, har ta kai sun mayar da soye-soyen zukatansu abin bautarsu. Wanda kuwa ya mayar da son zuciyarsa shi ne abin bautarsa, to shi Manzo (ﷺ) ba zai iya kare shi daga bin son zuciyar ba ya dawo da shi zuwa ga imani ya hana shi kafirci.
Sai kuma ya tabbatar masa cewa da dama daga cikin waɗanda yake yi musu wa’azi da kiran su zuwa ga Tauhidi ba sa sauraron sa sauraro na karɓa da aiki da abin da suke ji, ba kuma sa hankaltar hujjojin da yake ba su, domin sun zama tamkar dabbobi waɗanda ba sa fahimtar komai ba sa kuma hankaltar wata hujja. Allah ya nuna masa cewa ai su sun ma fi dabbobi ɓata, domin su dabbobi da ma Allah bai ba su guzurin hankali irin na ɗan’adam ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Inuwar da ɗan’adam yake gani a kullum wata babbar aya ce daga cikin ayoyin Allah masu nuna cikar Kudurarsa da Kaɗaitakarsa.

2. Samuwar haske daga hudowar alfijir har zuwa fitowar rana mai samar da inuwa wadda take raguwa kaɗan-kaɗan yayin da rana take ƙara ɗagawa sama har zuwa lokacin zawali, wannan ma wata babbar rahama ce ga halittar Allah, domin da Allah ya ga dama da sai ya sanya ƙasa da rana a kan wani tsari guda ɗaya wanda ba ya canzawa, don haka sai inuwa ta ci gaba da wanzuwa a tsaye ba gushewa. To amma Allah

ya san buƙatun da tsirrai da abubuwa masu rai suke da su na hasken rana domin kyautatuwarsu, don haka sai ya sanya yanayin yana sassauyawa.

3. Tunatar da ɗan'adam ni'imar samuwar dare a gare shi wanda a cikinsa ne yake samun sukuni da natsuwa a wuraren hutunsa.

4. Bacci wata babbar ni'ima ce ga ɗan'adam, kuma wata buƙata ce gare shi kamar buƙatar ci da sha, domin gaɓoɓinsa da suke aiki a tsawon yini suna buƙatar hutu da nutsuwa wadda hakan ba ya samuwa sai tare da bacci, don haka ne yake babbar ni'ima ga duk wani abu mai rai. Hakanan samuwarsa wata aya ce daga cikin ayoyin Allah, domin bacci ba a hannun ɗan'adam yake ba; wani lokaci yakan buƙace shi amma ya rasa shi, wani lokaci kuma ya so hira tsawon dare amma bacci ya hana shi.

5. Kaɗawar iska don sanar da kusantowar saukar ruwan sama aya ce daga cikin ayoyin Allah masu nuna cikar Kudurarsa. Allah yakan haɗa girgije ta hanyar kaɗawar iska kamar yadda yakan hallakar da waɗanda ya so hallakarwa da iskar.

6. Ruwan sama tsarkakakke ne mai tsarkakewa, baya ga albarka da ke cikinsa ta raya ƙasa bayan ta bushe sai ta fitar da tsirran cikinta da shuke-shukenta, sannan mutum da dabbobi su sami abin sha.

7. Sarrafa hujjoji da kawo su ta sigogi daban-daban hanya ce ta gamsar da mai sauraro.

Suratul Furƙan (45-50)

أَلَمْ تَرَ إِلَىٰ رَبِّكَ كَيْفَ مَدَّ ٱلظِّلَّ وَلَوْ شَآءَ لَجَعَلَهُۥ سَاكِنًا ثُمَّ جَعَلْنَا ٱلشَّمْسَ عَلَيْهِ دَلِيلًا ﴿٤٥﴾ ثُمَّ قَبَضْنَٰهُ إِلَيْنَا قَبْضًا يَسِيرًا ﴿٤٦﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى
جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ لِبَاسًا وَٱلنَّوْمَ سُبَاتًا وَجَعَلَ ٱلنَّهَارَ نُشُورًا ﴿٤٧﴾ وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ ٱلرِّيَٰحَ بُشْرًۢا بَيْنَ يَدَىْ رَحْمَتِهِۦ ۚ وَأَنزَلْنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً
طَهُورًا ﴿٤٨﴾ لِّنُحْـِۧيَ بِهِۦ بَلْدَةً مَّيْتًا وَنُسْقِيَهُۥ مِمَّا خَلَقْنَآ أَنْعَٰمًا وَأَنَاسِىَّ كَثِيرًا ﴿٤٩﴾ وَلَقَدْ صَرَّفْنَٰهُ بَيْنَهُمْ لِيَذَّكَّرُوا۟ فَأَبَىٰٓ أَكْثَرُ ٱلنَّاسِ إِلَّا كُفُورًا ﴿٥٠﴾

45. Shin ba ka ganin (irin aikin) Ubangijinka yadda ya shimfiɗa inuwa, da kuwa ya ga dama da sai ya sanya ta a tsaye cak, sannan Muka sanya rana dalilin samuwarta (inuwar).

46. Sannan Muka riƙa janye ta da kaɗan-kaɗan.

47. Kuma shi ne wanda ya sanya muku dare ya zama sutura, bacci kuma don hutawa kuma ya sanya rana don watsuwa (wajen neman abinci).

48. Kuma shi ne wanda ya aiko iska don albishir a gabanin (saukar) rahamarsa. Muka kuma saukar da ruwa mai tsarkakewa daga sama.

49. Don Mu raya busasshiyar ƙasa da shi, kuma Mu shayar da dabbobi da mutane masu yawa daga abubuwan da Muka halitta.

50. Haƙiƙa kuma Mun sarrafa shi a tsakaninsu don su wa'azantu, sai mafi yawan mutane suka ƙi (wa'azantuwa) sai kafirci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu daga cikin ayoyinsa da ni'imominsa waɗanda suke nuna cikar Kudurarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin Annabi (ﷺ) da cewa ya duba ya ga yadda Allah ya shimfiɗa inuwa a bayan ƙasa, da ya ga dama

da sai ya sanya ta a tsaye cak ba ta motsawa, ya kuma sanya rana ta zama dalilin samuwar inuwar ga abubuwa wadda kuma take ƙaruwa tana raguwa. Sannan kuma ya riƙa janye inuwar da kaɗan-kaɗan tana ta raguwa gwargwadon ɗagawar rana, har ta zamanto ta gushe gaba ɗaya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ni'imar samuwar dare ga ɗan'adam wanda yake a matsayin sutura a wurinsa wadda take suturce shi ta kuma suturce sauran abubuwa. Ya kuma sanya musu bacci don ya zamanto hutu gare su bayan sun yi ayyuka da rana sun gaji. Rana kuma ya sanya musu ita lokacin fitarsu zuwa ayyukansu na yau da gobe.
Akwai kuma wata babbar ni'ima da ya yi ga 'yan'adam mai ƙunshe da dalilan cikar Kudurar Allah, watau ita ce lokacin da yake aiko da iska don ta yi albishir da saukar ruwan sama wanda yake rahama ce ga bayin Allah. Ya kuma saukar da ruwa mai tsarki daga sama wanda mutane suke tsarkake jikinsu da tufafinsu da shi.
Allah ya bayyana cewa ya yi haka ne don ya raya busasshiyar ƙasa da wannan ruwan sai ta fitar da tsirranta da shuke-shuke iri-iri, kuma ya shayar da mutane da dabbobi da yawa da wannan ruwan.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya sarrafa hujjoji da dalilai daban-daban a cikin Alƙur'ani domin mutane su wa'azantu, to amma yawancinsu suka ƙi wa'azantuwa sai kafirce wa gaskiya da butulce masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gamewar manzancin Annabi (ﷺ) ga duniya baki ɗaya.

2. Da'awa da Alƙur'ani wani babban jihadi ne.

3. A aya ta 53 Allah ya bayyana girman Kudurarsa ta haɗa koguna biyu mai ruwan daɗi da mai ruwan zartsi, amma ya kare tsakaninsu ya hana su gaurayuwa da juna; mai zartsi ba zai ɓata mai daɗi ba. Wannan ayar tana iya shafar yanayin zamantakewar Musulmi da kafirai a Makka kafin hijira da haɗuwar muminai tare da kafirai suna maƙotakar juna, amma Allah ya tsare imanin Musulmi, mushirikai ba su iya cusa musu wani abu na kafirci a cikin imaninsu ba, kamar yadda ruwan zartsi bai iya gaurayuwa da na daɗi ba ya ɓata shi.

4. Hikimar auratayya tsakanin mutane, watau samun ƙarin kusanci da dangantaka ta hanyar aure.
Suratul Furƙan (51-55)
وَلَوۡ شِئۡنَا لَبَعَثۡنَا فِي كُلِّ قَرۡيَةٖ نَّذِيرٗا ٥١ فَلَا تُطِعِ ٱلۡكَٰفِرِينَ وَجَٰهِدۡهُم بِهِۦ جِهَادٗا كَبِيرٗا ٥٢ ۞وَهُوَ ٱلَّذِي مَرَجَ ٱلۡبَحۡرَيۡنِ هَٰذَا عَذۡبٞ فُرَاتٞ وَهَٰذَا مِلۡحٌ أُجَاجٞ وَجَعَلَ بَيۡنَهُمَا بَرۡزَخٗا وَحِجۡرٗا مَّحۡجُورٗا ٥٣ وَهُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ مِنَ ٱلۡمَآءِ بَشَرٗا فَجَعَلَهُۥ نَسَبٗا وَصِهۡرٗاۗ وَكَانَ رَبُّكَ قَدِيرٗا ٥٤ وَيَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُهُمۡ وَلَا يَضُرُّهُمۡۗ وَكَانَ ٱلۡكَافِرُ عَلَىٰ رَبِّهِۦ ظَهِيرٗا ٥٥

51. Da kuma Mun ga dama, lalle da mun aiko wani mai gargaɗi cikin kowacce alƙarya.

52. To kada ka bi son ran kafirai kuma ka yaƙe su da shi (Alƙur'ani) yaƙi mai girma.

53. Shi ne kuma wanda Ya haɗa koguna biyu: wannan mai tsananin daɗi wannan kuma mai tsananin zartsi, Ya kuma sanya shamaki a tsakaninsu da kuma kariya mai karewa.

54. Shi ne kuma wanda Ya halicci mutum daga ruwa sannan Ya mayar da shi dangantaka da surukuta. Ubangijinka Ya kasance Mai iko ne.

55. Kuma suna bauta wa wanin Allah abin da ba zai amfane su ba kuma ba zai cuce su ba. Kafiri kuwa ya kasance mai taimaka wa (Shaiɗan ne) a kan bijire wa Ubangijinsa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa da ya ga dama da sai ya rage wa Manzonsa (ﷺ) aiki ya aika wa kowace alƙarya da manzonta mai yi mata gargaɗi, to amma bai ga damar yin haka ba, sai ya aiko Annabi Muhammadu (ﷺ) shi kaɗai zuwa ga talikai baki ɗaya mutum da aljan, don ya ba shi babban matsayi a cikin annabawansa da manzanninsa.
Sai kuma ya gargaɗe shi da cewa kada ya yi wa kafirai biyayya a kan abin da suke nema a wajensa na yin sako-sako wajen kiran su zuwa ga Tauhidi, domin shigo-shigo-ba-zurfi ne suke yi masa, sai ya umarce shi da ya yaƙe su da Alƙur'anin da aka saukar masa yaƙi mai girma wanda yake cike da haƙuri da juriya wajen kiran su zuwa ga Allah.
Sannan Allah ya ci gaba da ambaton dalilan Kudurarsa da cikar ikonsa da cewa shi ne ya haɗa koguna biyu ɗaya mai ruwan daɗi ɗaya kuma mai zartsi, to amma kuma sai ya sanya shamaki a tsakaninsu wanda zai hana su gaurayuwa da juna.
Ya kuma bayyana cewa shi ne wanda ya halicci mutum daga ruwan maniyyin namiji da mace ya kuma samar da dangantaka ta jini da ta surukuta tsakanin mutane, don haka Ubangiji mai iko ne a kan komai babu abin da yake gagarar sa.
Sai kuma ya bayyana wautar kafirai masu bautar wasu ba Allah ba waɗanda ba za su amfane su da komai ba don sun yi musu biyayya, kuma ba za su cutar da su da komai ba don sun saɓa musu. To amma shi kafiri koyaushe yakan bi Shaiɗan ne a kan abin da zai jawo masa fushin Allah mahaliccinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babban aikin da Allah ya ɗora wa Manzonsa (ﷺ) shi ne yin albishir ga mutanen ƙwarai waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka na gari da kuma yin gargaɗi ga waɗanda suka ƙi imani suka bijire masa. Wannan aiki na albishir da gargaɗi suna nuni ne zuwa umarni da kyawawan ayyuka da sakamakonsu da kuma hana munanan ayyuka da bayanin mummunan sakamakon wanda ya aikata su.

2. Mai kira zuwa ga Allah ba ya neman mutane su biya shi ladan aikin da yake yi, domin yana yi ne don Allah, kuma wani nauyi ne a kansa da Allah ya ɗora masa yake saukewa.

3. Allah shi kaɗai ne wanda ya cancanta bawa ya dogara da shi cikin duk al'amuransa na addini da na rayuwa, domin shi ne wanda rayuwarsa ba ta da farko ba ta da ƙarshe, duk wani rai bayan shi mamaci ne.

4. Ba wanda Allah ya ɗora masa alhakin shiriyar bayinsa da imaninsu; wannan aiki ne na Allah shi kaɗai, shi ne ya san halin da kowa yake ciki shi kuma ne zai yi musu sakayya.

5. Tabbatar da siffar daidaito a kan Al'arshi ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), daidaiton da ya dace da shi ba tare da wani tawili ba ko korewa ko kwatance.

6. Babu wanda zai siffanta Allah kamar yadda shi zai siffanta kansa ko Manzonsa ya siffanta shi a cikin hadisansa ingantattu. Don haka wajibi ne ga Musulmi ya tabbatar wa da Allah siffofinsa waɗanda ya siffanta kansa da su ko Manzonsa (ﷺ) ya siffanta shi da su bisa sharaɗin da ya gabata.

7. Sunan Allah 'Arrahman' suna ne da babu wanda ya yi tarayya da Allah a cikinsa. Yana nuna siffantuwar Allah da siffar Rahma.

Suratul Furƙan (56-62)

وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا مُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ٥٦ قُلۡ مَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ مِنۡ أَجۡرٍ إِلَّا مَن شَآءَ أَن يَتَّخِذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلٗا ٥٧ وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱلۡحَيِّ ٱلَّذِي لَا يَمُوتُ وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِهِۦۚ وَكَفَىٰ بِهِۦ بِذُنُوبِ عِبَادِهِۦ خَبِيرًا ٥٨ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ ٱلرَّحۡمَٰنُ فَسۡـَٔلۡ بِهِۦ خَبِيرٗا ٥٩ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱسۡجُدُواْ لِلرَّحۡمَٰنِ قَالُواْ وَمَا ٱلرَّحۡمَٰنُ أَنَسۡجُدُ لِمَا تَأۡمُرُنَا وَزَادَهُمۡ نُفُورَۢا ٦٠ تَبَارَكَ ٱلَّذِي جَعَلَ فِي ٱلسَّمَآءِ بُرُوجٗا وَجَعَلَ فِيهَا سِرَٰجٗا وَقَمَرٗا مُّنِيرٗا ٦١ وَهُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ خِلۡفَةٗ لِّمَنۡ أَرَادَ أَن يَذَّكَّرَ أَوۡ أَرَادَ شُكُورٗا ٦٢

56. Kuma ba Mu aiko ka ba sai kawai don ka zama mai albishir mai gargaɗi gargaɗi.

57. Ka ce (da su): “Ba na tambayar ku wani lada a kansa (gargaɗin), sai dai ya rage ga wanda ya ga dama ya riƙi hanya (ta gari) zuwa ga Ubangijinsa.”

58. Kuma ka dogara ga (Allah) Rayayye Wanda ba zai mutu ba, kuma ka yi tasbihi da godiyar sa, kuma Ya isa Masani ga zunuban bayinsa.

59. (Shi ne) wanda Ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu cikin kwana shida, sannan Ya daidaita a kan Al’arshi. (Shi ne) Arrahmanu, sai ka tambayi Masani game da Shi.

60. Idan kuwa aka ce da su: “Ku yi sujjada ga Arrahmanu” sai su ce: “Mene ne Arrahmanu? Yanzu ma yi sujjada ga abin da kake umartar mu?” (Wannan umarnin) kuma ya ƙara musu fanɗarewa.

61. Wanda Ya sanya wuraren saukar taurari cikin sama, Ya kuma sanya mata rana mai haske da wata mai haskakawa, albarkatunsa sun yawaita.

62. Shi ne kuma wanda Ya sanya dare da rana masu maye wa juna ga wanda ya yi nufin ya wa’azantu ko kuma ya yi nufin godiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa bai aiko shi ba sai don ya zama mai albishir ga wanda ya yi masa ɗa’a da cewa yana da sakamako a wurin Allah na gidan Aljanna, ya kuma zama mai gargaɗi ga wanda ya saba masa da cewa yana da azaba ranar alƙiyama.
Sannan ya umarce shi da ya sanar da kafirai cewa ba ya neman su biya shi wani lada a kan isar da saƙon da yake yi musu, sai dai wanda ya ga dama ya ciyar da dukiyarsa don Allah domin neman yardarsa.
Sai kuma ya umarci Manzonsa da ya dogara ga Allah Rayayye wanda ba zai mutu ba har abada a cikin dukkan al’amuransa, ya kuma tsarkake shi daga duk wata tawaya da kasawa. Ya tabbatar masa cewa ya isa masanin komai game da zunubban bayinsa, babu abin da zai ɓuya gare shi, kuma zai yi musu sakayya a kai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikar ikonsa da cewa shi ne wanda ya halicci sammai da ƙasa da duk halittun da suke tsakaninsu cikin kwana shida, sannan ya daidaita a kan Al’arshi, daidaiton da ya dace da shi, kuma shi ne Allah mai rahama wanda rahamarsa ta yalwaci komai a sammai da ƙasa. Sai kuma ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya tambaye shi, (shi Allah), don ya sanar da shi siffofinsa na kamala da ɗaukaka domin shi ne masanin Zatinsa, babu wanda zai iya siffanta shi kamar yadda shi zai siffanta kansa da kansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kafircin mushirikai da yadda suke ƙaryata siffofin Allah maɗaukaka, da cewa idan aka umarce su da yin sujjada ga Allah mai rahama sai su ce: “Mene ne *Arrahmanu*”, watau suna musun a siffanta Allah da sunan *‘Arrahmanu’,* suna nuna wai su ba su san shi da wannan sunan ba, har ma su riƙa mamakin yaya za a umarce su da yin sujjada gare shi, alhalin su ba su san

wane ne mai wannan sunan ba. Wannan umarni da aka yi musu da kuma ambaton sunan Allah mai rahama sai ya ƙara musu fanɗarewa da guje wa imani da Allah.

An karɓo daga Miswar ɗan Makhrama (Allah ya ƙara masa yarda) cikin bayanin da ya ruwaito a kan *Sulhul Hudaibiyya* lokacin da Suhailu ɗan Amru ya zo za a rubuta takardar sulhu tsakanin Kuraishawa da Manzon Allah (ﷺ) , sai Annabi (ﷺ) ya ce wa mai rubutu ya rubuta: "*Bismillahir Rahmanir Rahim*", sai Suhailu ya yi farat ya ce:"Amma *Arrahman*, na rantse da Allah mu ba mu san shi ba, sai dai ya rubuta: "*Bismikal Lahumma*, kamar yadda kake rubutawa." Sai Musulmi suka ce: "Wallahi ba zai rubuta haka ba, sai dai ya rubuta: "*Bismillahir Rahmanir Rahim.*" Sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Rubuta *Bismikal Lahumma.*" [Bukhari #2731].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da siffanta kansa da bayanin girman Kudurarsa, da cewa shi ne wanda albarkatunsa da alheransa suka yawaita wanda kuma ya sanya masaukan taurari da kuma taurari masu gudu a sararin samaniya, ya kuma sanya rana mai haske a cikinta da kuma wata mai haskakawa wanda yake samun haskensa daga hasken rana.
Shi ne kuma Allah wanda ya sanya dare da rana suna maye gurbin juna; idan ɗaya ya tafi sai ɗayan ya zo ya maye gurbinsa. Ya bayyana cewa yana yin wannan aiki ne ga wanda yake nufin ya wa'azantu da ayoyin Allah ya sami shiriya, ko yake nufin gode wa Allah a bisa ɗimbin ni'imominsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zama bawan Allah wanda yake bautar Allah bisa ga so da yarda, babban matsayi ne da Allah yake bai wa wanda ya ga dama daga cikin bayinsa.

2. Yana daga cikin siffofin bayin Allah su zama masu tawali'u da haƙuri da biyayya ga Allah lokacin gafalar wasu mutane, da kuma tsoron Allah da tattali wajen ciyarwa da sauran al'amura.

3. Yana daga cikin siffofin bayin Allah guje wa shirka da nisantar kisan kai ba bisa haƙƙi ba, da nisantar zina da ƙarya, da ɗaukar izina daga ayoyin Allah.

4. Ayoyi da dama sun tabbatar da dawwama a wutar Jahannama ga wanda ya mutu yana bautar wanin Allah. Amma wanda ya mutu yana zina bai tuba ba ko ya yi kisan kai ya mutu ba tare da an yi masa ƙisasi ba, to waɗannan sun mutu a kan wani babban laifi da suka cancanci azaba mai tsanani a wutar Jahannama, amma daga ƙarshe za a fitar da su daga gare ta saboda imaninsu, kamar yadda nassoshi na Alƙur'ani da hadisai masu yawa suka nuna.

5. Allah ya ambaci waɗannan laifuka uku, watau shirka da kisan kai da zina domin suna daga cikin mafiya girman laifuffuka saboda shirka ɓarna ce a addini, kisa kuwa ɓarnar rayuka ne, zina kuwa ɓarna ce da ke shafar mutunci.

6. Kwaɗaitarwa a kan yin cikakkiyar tuba wadda mumini zai je gaba ga mahaliccinsa ya karɓi tubansa ya kuma saka masa da mafificin sakamako.

7. Tuba ta gari tana nufin barin aikata wannan saɓon da aka tuba saboda shi.

8. Haramcin zuwa wuraren da ake saɓon Allah a ciki, kamar wuraren da ake yin izgili da ayoyin Allah da wuraren da ake yin giba ko gulma ko kaɗe-kaɗe da raye-raye na haramun ko ake shan giya da sauran ayyuka na ashsha.

9. Duk waɗanda suka guje wa wuraren ɓarna da ƙarya to lalle kuwa ba za ka same su masu faɗar ƙarya ba, kuma ba za su yi shaidar zur ba, domin kuwa waɗannan suna cikin ababen da ayar ta ƙunsa.

10. Muhimmancin addu'ar iyaye ga 'ya'yansu a kan su zama na gari masu biyayya ga Allah da Manzonsa da riƙo da addininsu.

11. Zamantowar 'ya'ya na gari masu riƙo da addininsu shi ne zai sanya su zama masu faranta wa iyayensu rai.

12. Allah ba mai buƙatuwa ne ga imanin kafirai ba, don haka rashin yin imaninsu ba zai cutar da shi komai ba.

Suratul Furƙan (63-77)

وَعِبَادُ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلَّذِينَ يَمۡشُونَ عَلَى ٱلۡأَرۡضِ هَوۡنٗا وَإِذَا خَاطَبَهُمُ ٱلۡجَٰهِلُونَ قَالُواْ سَلَٰمٗا ٦٣ وَٱلَّذِينَ يَبِيتُونَ لِرَبِّهِمۡ سُجَّدٗا وَقِيَٰمٗا ٦٤ وَٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱصۡرِفۡ عَنَّا عَذَابَ جَهَنَّمَۖ إِنَّ عَذَابَهَا كَانَ غَرَامًا ٦٥ إِنَّهَا سَآءَتۡ مُسۡتَقَرّٗا وَمُقَامٗا ٦٦ وَٱلَّذِينَ إِذَآ أَنفَقُواْ لَمۡ يُسۡرِفُواْ وَلَمۡ يَقۡتُرُواْ وَكَانَ بَيۡنَ ذَٰلِكَ قَوَامٗا ٦٧ وَٱلَّذِينَ لَا يَدۡعُونَ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ وَلَا يَقۡتُلُونَ ٱلنَّفۡسَ ٱلَّتِي حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَلَا يَزۡنُونَۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ يَلۡقَ أَثَامٗا ٦٨ يُضَٰعَفۡ لَهُ ٱلۡعَذَابُ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَيَخۡلُدۡ فِيهِۦ مُهَانًا ٦٩ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ عَمَلٗا صَٰلِحٗا فَأُوْلَٰٓئِكَ يُبَدِّلُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِهِمۡ حَسَنَٰتٖۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٧٠ وَمَن تَابَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَإِنَّهُۥ يَتُوبُ إِلَى ٱللَّهِ مَتَابٗا ٧١ وَٱلَّذِينَ لَا يَشۡهَدُونَ ٱلزُّورَ وَإِذَا مَرُّواْ بِٱللَّغۡوِ مَرُّواْ كِرَامٗا ٧٢ وَٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ لَمۡ يَخِرُّواْ عَلَيۡهَا صُمّٗا وَعُمۡيَانٗا ٧٣ وَٱلَّذِينَ يَقُولُونَ رَبَّنَا هَبۡ لَنَا مِنۡ أَزۡوَٰجِنَا وَذُرِّيَّٰتِنَا قُرَّةَ أَعۡيُنٖ وَٱجۡعَلۡنَا لِلۡمُتَّقِينَ إِمَامًا ٧٤ أُوْلَٰٓئِكَ يُجۡزَوۡنَ ٱلۡغُرۡفَةَ بِمَا صَبَرُواْ وَيُلَقَّوۡنَ فِيهَا تَحِيَّةٗ وَسَلَٰمٗا ٧٥ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ حَسُنَتۡ مُسۡتَقَرّٗا وَمُقَامٗا ٧٦ قُلۡ مَا يَعۡبَؤُاْ بِكُمۡ رَبِّي لَوۡلَا دُعَآؤُكُمۡۖ فَقَدۡ كَذَّبۡتُمۡ فَسَوۡفَ يَكُونُ لِزَامٗا ٧٧

63. Bayin (Allah) Mai rahama kuwa (su ne) waɗanda suke tafiya a bayan ƙasa a natse; idan kuma wawaye sun yi musu magana (sai) su faɗa (musu) magana ta aminci.

64. (Su ne) kuma waɗanda suke kwana suna masu sujjada da tsayuwa ga Ubangijinsu.

65. (Su ne) kuma waɗanda suke cewa: "Ya Ubangijinmu, Ka kawar mana da azabar Jahannama; lalle azabarta ta kasance halaka ce mai ɗorewa.

66. "Lalle ita (Jahannama) ta kasance mummunar matabbata kuma mazauna (ga kafirai)."

67. (Su ne) kuma waɗanda idan suka ciyar ba sa almubazzaranci kuma ba sa yin ƙwauro, (ciyarwarsu) kuwa ta kasance tsaka-tsaki ce.

68. (Su ne) kuma waɗanda ba sa bauta wa wani tare da Allah, kuma ba sa kashe ran da Allah Ya hana kashewa sai da haƙƙi, kuma ba sa yin zina. Wanda kuwa ya aikata hakan to zai haɗu da (uƙubar) laifinsa.

69. Za a ninninka masa azaba ranar alƙiyama, kuma ya dawwama a cikinta a wulaƙance.

70. Sai dai wanda ya tuba ya kuma yi imani, kuma ya yi aiki na gari, to waɗannan Allah zai musanya munanan ayyukansu da kyawawa. Allah kuwa ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

71. Wanda kuwa ya tuba ya kuma yi aiki na gari, to lalle shi ne wanda yake tuba na gaskiya zuwa ga Allah.

72. (Su ne) kuma waɗanda ba sa halartar wuraren baɗala, idan kuma suka wuce ta wurin aikin assha to sai su wuce suna masu mutunta kansu.

73. (Su ne) kuma waɗanda idan aka yi musu wa'azi da ayoyin Ubangijinsu ba sa fuskantar su suna kurame kuma makafi.

74. (Su ne) kuma waɗanda suke cewa: "Ya Ubangijinmu, Ka ba mu masu sanyaya mana zukata daga matayenmu da zuri'armu, kuma Ka sanya mu abin koyi ga masu taƙawa.

75. Waɗannan su ne ake saka wa da ɗakuna na Aljanna saboda haƙurin da suka yi, za kuma a tare su a cikinta da gaisuwa da sallama.

76. Suna madawwama a cikinta. Matabbata da mazauni sun kyautata.

77. Ka ce: "Ba ruwan Ubangijina da ku in ba don ibadarku ba; to ga shi kun ƙaryata, to wannan (sakamakonsa) zai zama azaba ce mai ɗorewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta bayinsa na gari masu bautar sa da ikhlasi da kyawawan siffofi guda goma tare da bayanin gwaggwaban sakamako da ya tanadar musu a ranar alƙiyama.
Siffa ta farko, su bayin Allah ne mai rahama. Wannan yana nuna sun sami babban matsayi a wurinsa saboda bautarsu gare shi, domin sifar 'bawan Allah' siffa ce ta ƙololuƙar daraja da girmamawa ga bawa.
Siffa ta biyu, su ne masu tafiya a bayan ƙasa sannu a hankali, cikin natsuwa, babu girman kai ko ji-ji da kai ko wulaƙanta mutane.

An karɓo daga Aliyu ɗan Abu Ɗalibi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya kasance idan yana tafiya yana yin dama da hagu kamar mai gangarowa daga tudu, tun da nake ban taɓa ganin kamarsa ba." [Ahmad #746 da Tirmizi #3637].

An karɓo daga Abu Ƙatada (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan za ku tafi salla to kada ku tafi kuna gaggawa; ku tafi cikin nutsuwa, abin da kuka riska sai ku sallata, abin da kuwa ya kuɓuce muku sai ku cikashe." [Bukhari #635 da Muslim #603].
Siffa ta uku, su ne idan wasu wawaye suka yi musu maganar wauta da rashin hankali to ba sa ramawa sai dai su mayar musu magana mai kyau ta neman zaman lafiya.

An karɓo daga Nu'uman ɗan Muƙarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya zagi wani a gaban Manzon Allah, sai wanda aka zaga ya riƙa ce wa mai zagin sa: "Aminci ya tabbata a gare ka." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle akwai wani mala'ika a tsakaninku yana kare ka duk lokacin da wannan yake zagin ka sai ya ce masa: "A'a sai dai kai, kai ne ka fi cancantar wannan zagin." Idan kuma ɗayan ya ce: "Aminci ya tabbata a gare ka." sai mala'ikan ya ce: "A'a gare ka dai (ba gare shi ba) kai ne ka fi shi cancantar aminci." [Ahmad #23745].
Siffa ta huɗu, su ne waɗanda suke kwana suna bautar Allah, suna sallar ƙiyamullaili.

Siffa ta biyar, su ne waɗanda suke addu'a suna roƙon Allah da ya kawar musu da azabar Jahannama, saboda azabarta mai lazimta da dawwama ce ga duk wanda ya mutu kafiri bai tuba ba, sannan kuma ita matabbata ce kuma mazauni da ya yi matuƙar muni ga duk wanda zai zauna a cikinsa.
Siffa ta shida, su ne waɗanda idan suka ciyar da dukiyarsu ba sa almubazzaranci da bushasha da ita sannan kuma ba sa ƙwauro ga wanda ya wajaba su ba shi daga cikinta, don haka dai suna ciyarwarsu da kashe dukiyarsu tsaka-tsaki ba tare da almubazzaranci ko ƙwauro ba.
Siffa ta bakwai, su ne waɗanda ba sa bauta wa wani tare da Allah, watau suna tsantsanta bautarsu ga Allah shi kaɗai ba sa yin shirka. Hakanan ba sa kashe wani rai da Allah ya haramta kashe shi ba da wani haƙƙi ba, kuma ba sa yin zina. Allah ya bayyana cewa duk wanda ya yi shirka ko ya kashe rai ba da haƙƙi ba ko kuma ya yi zina, to zai haɗu da mummunar uƙuba a kan laifin da ya aikata. Kuma za a ninninka masa azaba a ranar alƙiyama ya dawwama a cikinta a wulaƙance.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na tambayi Manzon Allah cewa: "Wane zunubi ne ya fi girma?" Sai ya ce: "Ka sanya wa Allah kishiya alhali shi ya halicce ka." Sai na ce: "Sai kuma wanne?" Sai ya ce: "Ka kashe ɗanka don gudun ya ci tare da kai." Na ce: "Sai kuma me?" Sai ya ce: "Ka yi zina da matar maƙocinka." [Bukhari #4477 da Muslim #86].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hukuncin wanda ya tuba daga aikata waɗancan miyagun laifuffuka, ya yi nadama tare da alƙawarin ba zai koma gare su ba, ya kuma yi imani tare da kyakkyawan aiki wanda zai nuna gaskiyar tubansa, to sai Allah ya tabbatar wa da waɗanda suka yi haka cewa, zai musanya musu munanan ayyukansu da kyawawa, domin Allah ya tabbata mai gafara ne ga duk wanda ya tuba cikin bayinsa mai jin ƙan su ne.
Malamai sun ambaci fassara biyu game da canza munanan ayyukansu da kyawawa:
Magana ta farko, za a canza su daga aikata munanan aiki zuwa aikata kyakkyawan aiki.
Sa'idu ɗan Jubair ya ce: "Allah ya canja su daga masu bautar gumaka zuwa masu bautar Allah mai rahama; ya canza su daga yaƙar Musulmi zuwa yaƙar mushirikai; ya canza su daga masu auren mata mushirikai zuwa ga masu auren mata muminai."
Magana ta biyu, su kansu miyagun ayyukan da suka yi ne a baya Allah zai canja musu su zuwa kyawawa bayan sun tuba, saboda duk sanda ɗayansu ya tuba daga laifin da ya aikata a baya ya yi nadama ya nemi gafarar Allah, to sai wannan laifin ya juye ya koma ɗa'a. Don haka a ranar alƙiyama ko da zai gan shi rubuce a cikin littafinsa, to ba zai cutar da shi ba, kamar yadda bayaninsa zai zo cikin hadisin Abu Zarri (Allah ya ƙara masa yarda). [Dubi Ibn Kasir, Juzu'i na 6, shafi na 127].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar da cewa, duk wanda ya tuba ya nuna ƙwaƙƙwaran dalili a kan gaskiyar tubansa ta hanyar aikata kyawawan ayyuka da barin munana, to lalle wannan tuba ce karɓaɓɓiya a wurin Allah.

An karɓo daga Abu Zarri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle ni na san ɗan wuta na ƙarshe da zai fito daga cikinta da na ƙarshen shiga Aljanna. Za a zo da wani mutum gaban Allah sai Allah ya ce: "Ku ajiye manyan laifukansa gefe guda, ku yi masa tambaya a kan ƙananansu." Sai a ce masa: "A ranar kaza da kaza ka aikata kaza, a rana kaza kuma ka aikata kaza?" Sai ya ce: "E, na aikata." Ba zai iya musantawa ba. Sai a ce masa: "To kowanne mummunan aiki an musanya maka shi da kyakkyawa." Sai ya ce: "Ya Allah Ubangijina, na aikata wasu laifuffuka da ni ban gan su ba a nan." Sai Manzon Allah ya yi dariya har sai da fiƙoƙinsa suka fito. [Muslim #190].
Siffa ta takwas, su ne waɗanda ba sa halartar wuraren baɗala da saɓon Allah, idan kuma suka wuce ta wurin maganganu da ayyukan assha to sai su yi maza su wuce suna masu mutunta kawunansu, ba za su yarda su tsaya a aikata wannan aikin assha tare da su ba ko su tsoma baki cikin maganganun da ba su dace ba.

Siffa ta tara, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) su ne waɗanda idan aka tunatar da su da ayoyin Allah ba za su toshe kunnuwansu su ƙi sauraro ba, ba kuma za su rufe idanuwansu su ƙi kallon su ba.
Siffa ta goma, su ne waɗanda suke ta addu'a suna roƙon Allah ya nufe su da haihuwar 'ya'ya na gari masu tsoron Allah waɗanda za su riƙa ganin su suna faranta musu rai saboda nagartar tarbiyyarsu. Hakanan suna roƙon sa ya sanya su su zama abin koyi ga mutane masu taƙawa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗannan bayi nasa na gari da cewa su ne za a saka musu da ɗakuna maɗaukaka a Aljannar Firdausi saboda haƙurin da suka yi wajen ɗa'ar Allah. Mala'iku su tare su da gaisuwa da sallama. Za su kuma dawwama cikin ni'imomin Aljanna har abada. Allah ya bayyana cewa wannan wurin tabbata da wannan mazauni ya yi kyau matuƙa.
Sai kuma ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya sanar da kafirai cewa ba ruwan Allah da su in ba domin ɗa'arsu da ibadarsu ba, kuma ko da sun yi ba amfana za su yi da ita ba, hakanan ayyukansu na saɓon Allah ba cutar da shi da komai za su yi ba. Ba domin bayinsa na gari waɗanda suke bauta masa suna roƙon sa ba, da ba ruwansa da su, domin su sun ƙaryata Manzo, don haka sakamakon wannan ƙaryatawar zai zama azaba ce mai ɗorewa a gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin tsananin kwaɗayin Manzon Allah (ﷺ) a kan shiriyar al'ummarsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana nufin kowanne daga cikin bayinsa ya yi imani don zaɓinsa da gamsuwarsa, don haka bai saukar da wani abu da zai tilasta wa kowa sai ya yi imani ba ko da ba ya so. Da kuwa ya ga dama to da ya yi hakan.

3. Tsayar wa da kafirai hujjoji da ayoyi mabayyana bai amfana musu komai ba domin girman kansu da taƙadarancinsu ya hana su yin tunani a kan ayoyin Allah. Domin ayoyin da suke nuna ingancin abin da ake kiran su zuwa gare shi na Tauhidi da imani da tashi bayan mutuwa, ayoyi ne masu yawan gaske a cikin sammai da ƙasa, amma idanunsu sun makance ba sa ganin su, don haka suke ci gaba da shirka da ƙaryata Manzon Allah da tashin alƙiyama.

26-Suratush Shu’ara

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan da ta fi shahara da shi shi ne *Shu’ara*’ saboda ita kaɗai ce Sura wadda aka ambaci wannan lafazi a cikinta, watau ‘mawaƙa’.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
An saukar da wannan Sura ne kafin hijirar Annabi (ﷺ) zuwa Madina, watau gaba ɗayanta Sura ce *Makkiyya*. Wannan shi ne ra’ayin mafiya yawan malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba’in da bakwai (47) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta sauka bayan *Suratul Waƙi’ah* gabanin *Suratun Naml*.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta ɗari biyu da ashirin da bakwai (227) ne a lissafin mutanen Sham da na Kufa. Amma a lissafin mutanen Makka da na Madina ayoyinta ɗari biyu ne da ashirin da shida (226).

5. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne fito-na-fito da masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ), masu sukan saƙon da ya zo da shi, suna raunana duk wata hujjar da yake taƙama da ita.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Kwarzanta Alƙur’ani da kasancewarsa gagara-koyo da nuna wa kafiran Larabawa gajiyawarsu a kan su kawo wani abu da ya yi kama da shi. Sannan da lallashin Annabi (ﷺ) game da bijirewar da kafirai suke yi wa kira zuwa ga Tauhidi wanda Alƙur’ani yake yi musu.
• Tsoratar da su fushin Allah da uƙubarsa a kan kafircinsu ta hanyar ba su labaran abin da ya faru ga al’ummun da suka gabace su, kamar labarin mutanen Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
• Bayanin girman matsayin Alƙur’ani da shaidar da Ahlul-Kitabi suka bayar a kansa, tare da mayar wa mushirikai martani a kan soke-soken da suke yi wa Alƙur’ani, da tsarkake shi daga zama waƙa ko maganar shaiɗanu.
• Umarnin Manzon Allah (ﷺ) da ya gargaɗi danginsa na kusa da bayyana cewa babu wani nauyi a kansa sai isar da saƙo. Da dai sauran dalilai da aka bayyana a cikin Surar.

Suratus Shu'ara (1-9)

طسٓمٓ ۝١ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ۝٢ لَعَلَّكَ بَٰخِعٞ نَّفۡسَكَ أَلَّا يَكُونُواْ مُؤۡمِنِينَ ۝٣ إِن نَّشَأۡ نُنَزِّلۡ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ ءَايَةٗ فَظَلَّتۡ أَعۡنَٰقُهُمۡ لَهَا خَٰضِعِينَ ۝٤ وَمَا يَأۡتِيهِم مِّن ذِكۡرٖ مِّنَ ٱلرَّحۡمَٰنِ مُحۡدَثٍ إِلَّا كَانُواْ عَنۡهُ مُعۡرِضِينَ ۝٥ فَقَدۡ كَذَّبُواْ فَسَيَأۡتِيهِمۡ أَنۢبَٰٓؤُاْ مَا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ۝٦ أَوَ لَمۡ يَرَوۡاْ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ كَمۡ أَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوۡجٖ كَرِيمٍ ۝٧ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ۝٨ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ۝٩

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ṬA SIN MIM.

2. Waɗannan ayoyi ne na Littafi mabayyani.

3. Ko za ka kashe kanka ne don ba su zama muminai ba?

4. Da Mun ga dama da sai Mu saukar musu da aya daga sama sai wuyoyinsu su zamo masu ƙanƙan da kai gare ta.

5. Kuma ba wani wa'azi sabo da zai zo musu daga (Allah) Mai rahama sai sun kasance masu bijire masa.

6. To haƙiƙa sun ƙaryata, ba da daɗewa ba labaran aƙibar abin da suke yi wa izgili za su zo musu.

7. Shin ba su yi duba zuwa ga ƙasa ba, (su ga) dangogin tsirrai masu kyau nawa ne Muka tsirar daga cikinta?

8. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya (mai nuna cikar ikon Allah); kuma yawancinsu ba su zamanto masu imani ba.

9. Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi Mabuwayi ne, Mai rahama.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da wasu haruffa. Magana a kan irin waɗannan haruffa ta gabata a farkon *Suratul Baƙara*. Sannan Allah ya bayyana cewa waɗannan ayoyin Alƙur'ani ne mai bayyana ƙarya da gaskiya kuma bayani gamsasshe.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da lallashin Manzonsa game da damuwar da yake ciki ta bijirewar kafirai da ƙin ba da gaskiya da wannan Alƙur'ani da yake karanta musu, duk kuwa da bayyanar hujjarsa a fili. Ya nuna masa cewa ba daidai ne ya kashe kansa ba saboda damuwa don sun ƙi yin imani da Allah da kaɗaita shi. Allah ya tabbatar masa da cewa da ya ga dama da sai ya saukar musu da wata aya daga sama wadda za ta tilasta musu su miƙa wuya gare ta ko da ba sa so, to amma Allah bai yi haka ba, saboda irin wannan imani na dole ba shi da amfani a wurinsa; ya ƙyale su ne don ya jarraba su shin za su yi imani da gaibu ne, watau abin da ba su gan shi ba?
Allah kuma ya bayyana cewa su mushirikai babu wata faɗakarwa sabuwa da za ta zo musu daga Allah mai rahama wadda take ƙunshe da hujjoji masu nuna Kaɗaitakarsa da gaskiyar Manzonsa face sai sun bijire wa sauraronta da gaskata ta.
Allah ya tabbatar da cewa sun ƙaryata gaskiyar da Manzo (ﷺ) ya zo musu da ita, to amma fa su sani cewa ba da daɗewa ba tabbacin sakamakon abin da suke yi wa izgili zai zo musu, watau azaba za ta auka musu.
Sai kuma ya ja hankalinsu a kan su yi tunani da hankalinsu, su dubi ƙasa su ga yadda Allah ya fitar da dangogin tsirrai daga cikinta masu kyau masu kuma amfani. Allah ya tabbatar musu cewa a game da yadda

yake fito da tsirrai iri-iri ya raya ƙasa bayan mutuwarta ba shakka akwai bayyanannen dalili a kan Ƙudurar Allah ta sake raya matattu, to amma yawancinsu ba su zamanto masu yin imani ba. Sannan ya tabbatar wa da Manzo cewa Ubangijinsa lalle shi Mabuwayi ne babu abin da zai gagare shi, kuma mai tausayi ne ga bayinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin gaskiyar Manzo (ﷺ) ta hanyar ambaton mummunar aƙibar masu ƙaryata manzanninsu, don mutanensa su san cewa irin abin da ya faru ga waɗancan na farko su ma zai iya faruwa gare su.

2. Siffanta Fir'auna da mutanensa da zalunci ya tabbata, domin dukansu masu zaluntar kawunansu ne ta hanyar bautar wanin Allah da kuma zaluntar mutane ta hanyar bautar da Banu Isra'ila da muzguna musu da hana su haƙƙoƙinsu.

3. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ji tsoron Fir'auna da mutanensa su ƙaryata shi ne, domin ya san irin wannan saƙo da wuya ne mutanen da ya je musu da shi ba su ƙaryata shi ba, musamman da yake har an ba shi matsayin manzo, tabbas zai so ya ga aikin da aka ɗora masa ya yi nasara, domin idan har aka ƙaryata shi to aikin ya samu matsala.

4. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba ya jin tsoron kisa, sai dai yana jin tsoron kada wani abu ya hana shi isar da saƙonsa.

5. Jin tsoro na ɗabi'a halal ne ga annabawa, ba ya kore kamalar Tauhidi.

6. Duk wanda ya ga ba zai iya aiwatar da wani aiki da aka ɗora masa shi kaɗai ba, to babu laifi ya nemi wanda zai kama masa su yi aikin tare don su yi nasara.

7. An umarci Annabi Musa da Haruna su fara sanar da Fir'auna cewa su manzannin Ubangijin talikai ne, domin su nuna masa cewa shi ma halitta ce ta Allah, ba shi ne ubangiji ba kamar yadda yake da'awa. Kuma a nuna wa Ƙibɗawa masu bautar rana da sauran ababen bauta ba Allah ba cewa duk abubuwan bautar nasu halittu ne na Allah ba alloli ne ba.

8. Yana daga cikin ayyukan da aka ɗora wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fitar da Banu Isra'ila daga ƙasar Fir'auna domin 'yanta su daga bauta da zalunci.

Suratus Shu'ara (10-17)

وَإِذۡ نَادَىٰ رَبُّكَ مُوسَىٰٓ أَنِ ٱئۡتِ ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٠ قَوۡمَ فِرۡعَوۡنَۚ أَلَا يَتَّقُونَ ١١ قَالَ رَبِّ إِنِّيٓ أَخَافُ أَن يُكَذِّبُونِ ١٢ وَيَضِيقُ صَدۡرِي وَلَا يَنطَلِقُ لِسَانِي فَأَرۡسِلۡ إِلَىٰ هَٰرُونَ ١٣ وَلَهُمۡ عَلَيَّ ذَنۢبٞ فَأَخَافُ أَن يَقۡتُلُونِ ١٤ قَالَ كَلَّاۖ فَٱذۡهَبَا بِـَٔايَٰتِنَآۖ إِنَّا مَعَكُم مُّسۡتَمِعُونَ ١٥ فَأۡتِيَا فِرۡعَوۡنَ فَقُولَآ إِنَّا رَسُولُ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٦ أَنۡ أَرۡسِلۡ مَعَنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ١٧

10. Kuma (ka tuna) lokacin da Ubangijinka Ya kira Musa cewa: "Ka tafi wajen mutanen nan azzalumai.

11. "(Watau) mutanen Fir'auna. Yanzu ba za su kiyaye dokokin Allah ba?"

12. (Musa) ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ni ina tsoron su ƙaryata ni.

13. “Kuma ƙirjina yana ƙuntata, kuma harshena ba ya sakuwa, sai Ka aika zuwa ga (ɗan’uwana) Haruna.

14. “Ni kuma akwai wani laifi da na yi musu, sai nake tsoron su kashe ni.”

15. (Allah) Ya ce: “A’a; (ba abin da zai same ka), sai ku tafi (kai da ɗan’uwanka) da ayoyinmu; lalle Mu masu jin (komai da zai faru) ne tare da ku.

16. “Ku je wajen Fir’auna sai ku faɗa masa cewa: ‘Lalle mu manzannin Ubangijin talikai ne.

17. “‘Cewa, ka sako mana da Banu-Isra’ila’.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin Annabi Musa da Haruna lokacin da aka aike su zuwa ga Fir’auna da mutanensa suka ƙaryata su, Allah kuwa ya hallakar da su don su zama izina da darasi ga duk waɗanda za su ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da ya aiko musu.
Allah ya tunatar da Annabi (ﷺ) lokacin da ya umarci Annabi Musa da ya tafi wajen azzaluman mutanen nan waɗanda suka kafirce wa Allah suka bautar da Banu-Isra’ila, watau Fir’auna da mutanensa, ya je ya yi musu wa’azi cikin lalama da tausasa magana cewa, yanzu ba za su yi taƙawa ba, watau su yi aiki da umarnin Allah su kuma guje wa haninsa?
Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kawo wa Allah uzurinsa ya nemi ya ƙarfafe shi da mataimaki wanda zai taya shi isar da saƙonsa, saboda yana jin tsoron za su ƙaryata shi, kuma ga ƙirjinsa yana ƙuntata saboda saurin fushi daga abin da suke aikatawa; sannan kuma harshensa ba ya sakuwa ya yi magana yadda ya kamata. Don haka ya roƙi Allah ya aika wa ɗan’uwansa Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Mala’ika Jibrilu don su haɗu tare su isar da wannan saƙo zuwa ga Fir’auna da mutanensa.
Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ƙara kawo wani uzurinsa na huɗu, da cewa ya yi wa Fir’auna da mutanensa laifi na kashe wani Baƙibɗe, don haka yana jin tsoron idan sun kama shi za su kashe shi don ɗaukar fansar ɗan’uwansu. To don gudun kada isar da saƙon ya samu tangarɗa idan an kashe shi yake neman su zama su biyu shi da ɗan’uwansa Haruna.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwantar wa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) hankali, da cewa ba za su kashe shi ba kuma an karɓa masa roƙonsa an haɗa shi da ɗan’uwansa don su isar da wannan manzanci tare, don haka kai-tsaye su tafi da ayoyin da aka ba su masu nuna gaskiyar manzancinsu, kamar sanda da hannunsa mai haske da sauran ayoyi tara da aka ba wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah ya tabbatar musu da cewa yana tare da su da nasararsa da goyon bayansa, yana kuma jin duk abin da zai gudana tsakaninsu da Fir’auna da mutanensa babu abin da zai kuɓuce masa.
Allah ya umarci Annabi Musa da ɗan’uwansa Haruna su je wurin Fir’auna su bayyana masa ƙarara cewa su manzanni ne daga Allah Ubangijin talikai, don haka ya sako musu Banu Isra’ila da yake tsare da su yana azabtar da su tare da bautar da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Fir’auna ya ɗauki laifin kisan kai da Musa ya yi a matsayin hujjar da ke nuna ƙaryar manzancinsa, to amma Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna masa aikata wannan laifin bisa kuskure ba shi ne hujjar cewa ƙarya yake ba.

2. Kurakuran mai wa’azi da ya riga ya aikata a baya, da kyautatawar da aka yi masa ba za su hana ya yi wa wanda ya yi kuskuren wa’azi ko wanda ya kyautata masa a baya ba.

3. Babu laifi mai daʾawa ya ɗauki matakan tsaron kansa daga sharrin maɓiyansa; yin haka ba ya kore tawakkali ko ya tauye shi.

Suratus Shuʾara (18-22)
قَالَ أَلَمۡ نُرَبِّكَ فِينَا وَلِيدٗا وَلَبِثۡتَ فِينَا مِنۡ عُمُرِكَ سِنِينَ ١٨ وَفَعَلۡتَ فَعۡلَتَكَ ٱلَّتِي فَعَلۡتَ وَأَنتَ مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ١٩ قَالَ فَعَلۡتُهَآ إِذٗا وَأَنَا۠ مِنَ ٱلضَّآلِّينَ ٢٠ فَفَرَرۡتُ مِنكُمۡ لَمَّا خِفۡتُكُمۡ فَوَهَبَ لِي رَبِّي حُكۡمٗا وَجَعَلَنِي مِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٢١ وَتِلۡكَ نِعۡمَةٞ تَمُنُّهَا عَلَيَّ أَنۡ عَبَّدتَّ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٢٢

18. (Fir'auna) ya ce: "Yanzu ba mu muka raine ka a cikinmu tun kana jariri ba, kuma ka zauna ka yi wasu shekaru na rayuwarka a cikinmu?

19. "Ka kuma aikata aika-aikarka da ka aikata alhali kuwa kana daga masu butulce wa (ni'imata)?"

20. (Musa) ya ce: "Na aikata haka ne a lokacin ina cikin marasa shiriya (ta rashin wahayi).

21. "Sannan na guje muku lokacin da na tsorata da ku, sai Ubangijina Ya ba ni kyautar ilimi Ya kuma sanya ni daga manzanni.

22. "Waccen ni'imar kuwa da kake goranta min ita saboda ka bautar da Bani-Isra'ila ne."

Bayan Annabi Musa da ɗan'uwansa Haruna sun zama annabawa sai suka tafi fadar Fir'auna suka nemi iso aka yi musu, suka same shi suka isar masa da saƙon da Allah ya umarce su da su isar masa. A nan ne fa sai Fir'auna ya goranta wa Annabi Musa da cewa ba su ne suka raine shi ba tun yana ɗan jariri har ya girma, ya kuma zauna a cikinsu tsawon shekaru suna kula da shi suna kyautata masa, sai kuma kwatsam da rana tsaka ya zo yana cewa wai shi manzo ne daga Allah? Fir'auna kuma ya tuna masa da laifin da ya yi na kashe Baƙibɗe lokacin da suke faɗa da wani Ba'isra'ile yana mai tuhumar sa da butulcin kyautatawar da aka yi masa a gidan Fir'auna.
Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tabbatar wa Fir'auna cewa, haka ne, ya san ya kashe Baƙibɗe, to amma a lokacin da abin ya faru da shi yana cikin halin rashin sani ne domin ba a fara yi masa wahayi ba a lokacin. Don haka sai ya gudu zuwa garin Madyana don tsoron kada shi ma su kashe shi; to a can ne Allah ya ba shi ilimi ya mayar da shi Manzo ya kuma aiko shi zuwa ga mutane.
Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya mayar wa Fir'auna martanin gorin tarbiyyar da ya yi masa da kuma barin sa da rai bai kuma bautar da shi ba kamar yadda ya yi wa sauran Banu Isra'ila, wannan kulawar da ya ba shi ba za ta hana shi yi masa wa'azi ba da gaya masa gaskiya, domin saƙon Allah ne, dole ya isar da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittun da Allah ya yi a sama da ƙasa ƙarfafan dalilai ne masu tabbatar da Rububiyyarsa da Kaɗaitakarsa.

2. Rashin hujja ko rauninta su ne ke sa a yi amfani da ƙarfi wajen zartar da wani ra'ayi na kama-karya.

3. Maganar Annabi Musa cewa: "Ku zamanto masu hankalta", wani martani ne ya mayar musu na jifansa da suka yi da motsuwar hankali. Watau su ne mahaukata, domin hankalinsu ne ya gushe har suke musun samuwar mahaliccin sammai da ƙassai da abin da yake tsakaninsu.

4. Yayin da Annabi Musa ya kirawo Fir'auna da tattausar magana amma shi kuma ya munana ladabinsa wajen ba shi amsa, shi ya sa Annabi Musa ya rufe hujjarsa ta uku da cewa: "...In kun zamanto masu hankalta". Ita ma Magana ce mai zafi. Watau da suna da hankali da sun fahimci abin da yake faɗa musu.

5. Ƙoƙarin tunzura wawaye da zuga su don su cutar da masu kira zuwa ga addini, daɗaɗɗen salo ne na azzaluman shugabanni.

Suratus Shu'ara (23-31)

قَالَ فِرۡعَوۡنُ وَمَا رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢٣ قَالَ رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَآۖ إِن كُنتُم مُّوقِنِينَ ٢٤ قَالَ لِمَنۡ حَوۡلَهُۥٓ أَلَا تَسۡتَمِعُونَ ٢٥ قَالَ رَبُّكُمۡ وَرَبُّ ءَابَآئِكُمُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٢٦ قَالَ إِنَّ رَسُولَكُمُ ٱلَّذِيٓ أُرۡسِلَ إِلَيۡكُمۡ لَمَجۡنُونٞ ٢٧ قَالَ رَبُّ ٱلۡمَشۡرِقِ وَٱلۡمَغۡرِبِ وَمَا بَيۡنَهُمَآۖ إِن كُنتُمۡ تَعۡقِلُونَ ٢٨ قَالَ لَئِنِ ٱتَّخَذۡتَ إِلَٰهًا غَيۡرِي لَأَجۡعَلَنَّكَ مِنَ ٱلۡمَسۡجُونِينَ ٢٩ قَالَ أَوَلَوۡ جِئۡتُكَ بِشَيۡءٖ مُّبِينٖ ٣٠ قَالَ فَأۡتِ بِهِۦٓ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٣١

23. Fir'auna ya ce: "To wane ne Ubangijin talikai?"

24. (Musa) ya ce: "(Shi ne) Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, idan har kun kasance masu sakankancewa (da hakan)".

25. (Fir'auna) ya ce da waɗanda suke kewaye da shi: "Shin ba kwa jin (abin da yake faɗa)?"

26. (Musa) ya ce: "Shi ne Ubangijinku kuma Ubangijin iyayenku na farko!"

27. (Fir'auna) ya ce: "Lalle Manzon da aka aiko muku tabbas mai taɓin hankali ne!"

28. (Musa) ya ce: "(Shi ne) Ubangijin mahudar rana da mafaɗarta da kuma abin da yake tsakaninsu; in kun zamanto masu hankalta."

29. (Fir'auna) ya ce: "Na rantse in har ka riƙi wani abin bauta ba ni ba, tabbas zan jefa ka cikin 'yan kurkuku!"

30. (Musa) ya ce: "Ko da na zo maka da wani abu bayyananne?"

31. (Fir'auna) ya ce: "To ka zo da shi dîn in ka kasance daga masu gaskiya."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin isgilin da Fir'auna ya fara yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da da'awarsa ta a bauta wa Allah shi kaɗai, inda ya tambayi Annabi Musa wai wane ne ma Ubangijin halittu wanda yake nuna musu shi ya aiko shi, kuma ya ce a bauta masa shi kaɗai? Watau a nan Fir'auna yana nuna masa cewa shi bai yarda da akwai wani Ubangiji in ba shi ba.
Sai muhawara ta ci gaba, Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya amsa wa Fir'auna da cewa Ubangijin halittu shi ne Ubangijin sammai da ƙasa da duk abin da yake tsakaninsu, don haka Fir'auna shi da mutanensa lallai su yi imani da shi su bauta masa shi kaɗai idan har sun kasance masu sakankancewa da haka.
Wannan ƙaƙƙarfar amsa ta Annabi Musa da ya ba wa Fir'auna ba ta yi wani tasiri ba; kamar ma ba da shi yake magana ba, sai kawai ya juya wajen fadawansa yana tambayar su wai suna kuwa jin abin da Musa yake faɗa?

Sai Annabi Musa ya ƙara tabbatar musu da cewa, Allah shi ne Ubangijinsu kuma Ubangijin iyayensu da kakanninsu na farko. Watau yana tabbatar musu da cewa shi Fir'auna ba ubangijin kowa ba ne, shi ma kansa bawan Allah ne wanda kuma shi ne mahaliccin sammai da ƙasa da duk abin da suka ƙunsa na halittu. Sai Fir'auna ya shiga nadẽ tabarmar kunya da hauka, domin ya rasa irin amsar da zai ba wa Annabi Musa, sai kawai ya shiga gaya wa fadawansa wai manzon da aka aiko musu fa mahaukaci ne yana fadar abin da ba zai taɓa shiga hankali ba.

To amma Annabi Musa bai daka ta tasa ba, sai ya ci gaba da fadi masa gaskiya da hujja mai ƙarfi, da cewa Allah wanda yake kiran su da su bauta masa shi ne Ubangijin mahudar rana kuma Ubangijin mafadar rana da abin da yake tsakaninsu, idan har suna da hankali to ya kamata su fahimci haka. Watau ya nuna musu cewa shi ne yake magana ta hankali wadda sai mai hankali zai gane, don haka shi ba mai taɓin hankali ne ba.

Yayin da Fir'auna ya ga tusa ta ƙure wa bodari sai ya fara barazana da nuna amfani da ƙarfin mulkinsa da rashin tausayinsa, yana yi wa Annabi Musa barazana da cewa, lalle idan har ya riƙi wani abin bauta ba shi ba, to lalle zai jefa shi gidan kurkuku ya gana masa azaba tare da fursunoni.

Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) dai bai ji tsoron barazanar Fir'auna ba, sai ma ya jefa masa wata hujja da cewa, yanzu sai ya jefa shi kurkuku ko da kuwa ya zo masa da wata hujja bayyananna wadda take tabbatar da abin da ya zo da shi gaskiya ne daga Allah?

To lokacin da Fir'auna ya ji wannan maganar daga Annabi Musa sai ya umarce shi da ya kawo hujjar da take nuna cewa shi mai gaskiya ne, domin ba ya zaton akwai wata mu'ujiza da Annabi Musa zai iya nuna masa.

Daga wadannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Fir'auna ya yaudari mutanensa don ya fahimci raunin hankulansu, ya nuna musu cewa abin da Annabi Musa ya zo da shi sihiri ne, su kuwa sun yi imani da tasirin sihiri da masu yinsa, suna iya aikata abubuwan ban mamaki wadanda mutane ba za su iya aikatawa ba. Sai ya tsoratar da su cewa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana amfani ne da wannan sihiri nasa domin ya kore su daga ƙasarsu da gidajensu. Fir'auna kuma ya yi haka ne domin ya cusa musu ƙiyayyar Annabi Musa a zukatansu su hadu su yaƙe shi tare.

2. Yana daga cikin dabi'ar miyagun shugabanni masu mulkin kama-karya da zalunci ga talakawansu, duk lokacin da suka tsinci kawunansu cikin wata babbar matsala da ta fi ƙarfinsu sai su komo ga talakawansu wadanda suke gasa wa aya a hannu, su dinga lallashin su da maganganu na ƙasƙantar da kai don neman hadin kansu don su iya magance matsalar da ta taso musu.

3. Yana daga cikin ludufin Allah da ya nuna wa bayinsa ƙaryar da Fir'auna ya yi musu na cewa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) mai sihiri ne, Allah kuma ya nufi su ba da shawarar a tattaro gwanayen sihiri daga ko'ina cikin ƙasar Masar domin a tara dandazon jama'a kowa ya nuna abin da yake tare da shi. Daga nan kuma sai gaskiya ta bayyana, masana tsafi da kansu suka tabbatar da ingancin abin da Annabi Musa ya zo da shi kuma suka yarda cewa ba sihiri ne ba.

Suratus Shu'ara (32-37)

فَأَلْقَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِيَ ثُعْبَانٌ مُّبِينٌ ﴿٣٢﴾ وَنَزَعَ يَدَهُۥ فَإِذَا هِيَ بَيْضَآءُ لِلنَّٰظِرِينَ ﴿٣٣﴾ قَالَ لِلْمَلَإِ حَوْلَهُۥٓ إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٌ عَلِيمٌ ﴿٣٤﴾ يُرِيدُ أَن يُخْرِجَكُم مِّنْ أَرْضِكُم بِسِحْرِهِۦ فَمَاذَا تَأْمُرُونَ ﴿٣٥﴾ قَالُوٓاْ أَرْجِهْ وَأَخَاهُ وَٱبْعَثْ فِى ٱلْمَدَآئِنِ حَٰشِرِينَ ﴿٣٦﴾ يَأْتُوكَ بِكُلِّ سَحَّارٍ عَلِيمٍ ﴿٣٧﴾

32. Sannan (Musa) ya jefa sandarsa sai ga ta (ta zama) kumurci ƙuru-ƙuru.

33. Ya kuma zaro hannunsa (daga cikin rigarsa) sai ga shi fari fat ga masu gani.

34. (Sai Firʾauna) ya ce da manyan mutanen da ke kewaye da shi: "Lalle wannan tabbas mai sihiri ne ƙwararre.

35. "Yana nufi ne ya fitar da ku daga ƙasarku da sihirinsa, to da me za ku yi umarni?"

36. Suka ce: "Ka dakatar da shi tare da ɗanʾuwansa, kuma ka aika manzanni cikin birane su tattaro maka (masu sihiri).

37. "Su zo maka da duk wani mai sihiri ƙwararre."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana yadda Firʾauna ya nemi Annabi Musa ya kawo hujjarsa, shi kuma sai ya jefar da sandarsa ƙasa sai kawai ta zama ƙaton kumurci a fili ƙuru-ƙuru babu wata alamar rufa-ido ko siddabaru. Ya kuma shigar da hannunsa cikin wuyan rigarsa sai ga shi ya fito da shi fari fat yana haske ba kuma irin hasken mai cutar albaras ba, kowa da kowa yana gani.
Firʾauna na ganin ayoyin da Annabi Musa ya nuna nan take sai ya ƙaryata shi, ya nuna taurin kansa, kuma ya yi yawo da hankalin `yan majalisarsa da faɗa musu abubuwa uku:
Na farko, ya tabbatar musu cewa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ƙwararren mai sihiri ne, don haka kada wannan sihiri nasa ya yaudare su.
Na biyu, ya tunzura mutanensa ta hanyar faɗa musu cewa manufar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ita ce ya fitar da su daga ƙasarsu ta hanyar amfani da sihirinsa, ya ja hankalin mutane ya tara mabiya su haɗu su ƙwace ƙasa daga hannunsu.
Na uku, ya nemi su ba shi shawarar abin da ya kamata ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da nufin ya ja hankalinsu don su haɗa ƙarfi su yaƙe shi. Amma kuma sanannen abu ne cewa Firʾauna ba ya jin shawarar kowa ballantana har ya nemi a ba shi shawara.
Amma duk da haka manyan fadawansa sun ba shi shawarar cewa ya jinkirta da ɗaukan wani mataki a kan Annabi Musa da ɗanʾuwansa Haruna, kada ya gaggauta azabtar da su har sai ya aika cikin ilahirin masarautarsa koʾina da koʾina an tattaro masa ƙwararrun masu sihiri, domin su yi gaba da gaba da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) su kuma zo masa da dangogin sihiri daban-daban waɗanda za su nuna masa iyakarsa da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alaƙar maɓarnata alaƙa ce kawai ta abin duniya da maslahar rayuwa.

2. Ɗabiʾar ruɗaɗɗu waɗanda son zuciya ya makantar da su ba sa ganin yadda abubuwa suke canzawa koyaushe suna ɗaukar son zuciyarsu ne zai yi nasara don, haka ba sa yin wani tanadi don gudun faruwar akasinsa.

3. Matsafa sun fara gudanar da sihirinsu da neman albarkar Firʾauna. Ko kuma a ce sun yi rantsuwa ne da buwayarsa a kan cewa za su yi galaba domin cikakkiyar amincewarsu da cewa babu wanda ya isa ya hana Firʾauna yin galaba.
4. Rantsuwa da wanin Allah kamar wani gunki ko rayuwar wani, wannan alʾada ce ta jahiliyya.

5. Firʾauna ya fito ba kunya ba tsoron Allah yana tuhumar masu sihiri bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi galaba a kansu da cewa shi ne babbansu wanda ya koya musu sihiri, duk da

cewa shi ne da kansa ya gayyato su kuma ya yi aiki da shawarar manyan fadawansa kafin ya gayyato su daga duk garuruwan Masar. Kuma sun san cewa ba su taɓa haɗuwa da Annabi Musa ba kafin wannan ranar, ba su ma taɓa ganin sa ba sam-sam, amma kuma duk da haka manyan fadawansa suka yarda da maganarsa, alhalin su karan kansu sun san ƙarya yake. Don haka ba wani abin mamaki ne ba a ga masu irin wannan hankalin sun ƙi yin imani da gaskiya bayan ta fito fili ƙarara tare da hujjoji da ayoyi bayyanannu.

6. Imanin masu sihiri babban dalili ne da yake tabbatar da cewa lalle Allah shi ne mai jujjuya zukata yadda ya ga dama a sanda ya ga dama.

Suratus Shu'ara (38-51)

فَجُمِعَ ٱلسَّحَرَةُ لِمِيقَٰتِ يَوۡمٖ مَّعۡلُومٖ ﴿٣٨﴾ وَقِيلَ لِلنَّاسِ هَلۡ أَنتُم مُّجۡتَمِعُونَ ﴿٣٩﴾ لَعَلَّنَا نَتَّبِعُ ٱلسَّحَرَةَ إِن كَانُواْ هُمُ ٱلۡغَٰلِبِينَ ﴿٤٠﴾ فَلَمَّا جَآءَ ٱلسَّحَرَةُ قَالُواْ لِفِرۡعَوۡنَ أَئِنَّ لَنَا لَأَجۡرًا إِن كُنَّا نَحۡنُ ٱلۡغَٰلِبِينَ ﴿٤١﴾ قَالَ نَعَمۡ وَإِنَّكُمۡ إِذٗا لَّمِنَ ٱلۡمُقَرَّبِينَ ﴿٤٢﴾ قَالَ لَهُم مُّوسَىٰٓ أَلۡقُواْ مَآ أَنتُم مُّلۡقُونَ ﴿٤٣﴾ فَأَلۡقَوۡاْ حِبَالَهُمۡ وَعِصِيَّهُمۡ وَقَالُواْ بِعِزَّةِ فِرۡعَوۡنَ إِنَّا لَنَحۡنُ ٱلۡغَٰلِبُونَ ﴿٤٤﴾ فَأَلۡقَىٰ مُوسَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِيَ تَلۡقَفُ مَا يَأۡفِكُونَ ﴿٤٥﴾ فَأُلۡقِيَ ٱلسَّحَرَةُ سَٰجِدِينَ ﴿٤٦﴾ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ﴿٤٧﴾ رَبِّ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ﴿٤٨﴾ قَالَ ءَامَنتُمۡ لَهُۥ قَبۡلَ أَنۡ ءَاذَنَ لَكُمۡۖ إِنَّهُۥ لَكَبِيرُكُمُ ٱلَّذِي عَلَّمَكُمُ ٱلسِّحۡرَ فَلَسَوۡفَ تَعۡلَمُونَۚ لَأُقَطِّعَنَّ أَيۡدِيَكُمۡ وَأَرۡجُلَكُم مِّنۡ خِلَٰفٖ وَلَأُصَلِّبَنَّكُمۡ أَجۡمَعِينَ ﴿٤٩﴾ قَالُواْ لَا ضَيۡرٌۖ إِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا مُنقَلِبُونَ ﴿٥٠﴾ إِنَّا نَطۡمَعُ أَن يَغۡفِرَ لَنَا رَبُّنَا خَطَٰيَٰنَآ أَن كُنَّآ أَوَّلَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ﴿٥١﴾

38. Sai aka tattara masu sihirin (don su zo) a ƙayyadajjiyar rana sananniya.

39. Aka kuma ce da mutane: "Shin za ku tattataro.

40. "Don mu goyi bayan masu sihiri idan har sun kasance su ne masu galaba?"

41. Sannan lokacin da masu sihirin suka zo sai suka ce da Fir'auna: "Shin muna da wani lada (da za ka ba mu) in har mun zama mu ne masu galaba?"

42. (Fir'auna) ya ce: "Na'am, kuma ma idan haka ya faru, to tabbas za ku zama daga makusanta."

43. (Sai Musa) ya ce da su: "Ku jefa duk abin da za ku jefa."

44. Sai suka jefa igiyoyinsu da sandunansu suka kuma ce: "Lalle da izzar Fir'auna tabbas mu ne masu galaba."

45. Sai Musa ya jefa sandarsa, sai ga ta tana lanƙwame duk abin da suke ƙagowa (na sihiri).

46. Sai aka durƙusar da masu sihirin suna masu sujjada.

47. Suka ce: "Mun yi imani da Ubangijin talikai.

48. "Ubangijin Musa da Haruna."

49. (Sai Fir'auna) ya ce: "Yanzu kwa yi imani da shi tun kafin in ba ku izini? Lalle tabbas shi ne babbanku wanda ya koya muku sihiri; to tabbas kuwa kwa sani. Lalle zan yanyanke hannayenku da ƙafafuwanku a tarnaƙe, kuma tabbas zan gicciye ku gaba ɗaya!"

50. Sai suka ce: “Ai ba damuwa; lalle mu masu komawa ne zuwa ga Ubangijinmu.

51. “Lalle mu muna kwaɗayin Ubangijinmu Ya gafarta mana kurakuranmu saboda zamantowarmu farkon muminai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Firʾauna ya karɓi shawarar manyan fadawansa, don haka an tattaro masa ƙwararrun masu sihiri an kuma tsayar da shawarar su haɗu da Annabi Musa a wani wuri da lokaci ƙayyadajje, watau ranar bikin idinsu. Aka kuma yi wa mutane shela aka nuna musu muhimmancin kowa ya halarta domin ya ga yadda za a ƙure sihirin Annabi Musa hujjar masu sihiri ta bayyana ta yi rinjaye, sai a goyi bayansu a ci gaba da zama a kan addinin Firʾauna da bautar sa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yayin da masu sihiri suka iso fadar Firʾauna sai suka gana da shi da farko don su tabbatar zai ba su ladansu idan sun sami galaba a kan Annabi Musa. Shi kuwa Firʾauna ya tabbatar musu da cewa lalle za su sami ladansu, bayan haka ma zai ƙara musu da janyo su kusa da shi a fadarsa don su zama masu ba shi shawara.
Daga nan masu sihiri suka hallara wajen taro suka tambayi Annabi Musa cewa su ne za su fara jefa kayan tsafinsu ko kuma shi ne zai fara? Sai ya umarce su da su fara jefa abin da suka yi niyyar jefawa, domin ya tabbatar da cewa shi abin da Allah ya ba shi ba sihiri ne ba muʾujiza ce. Sai suka jefa igiyoyinsu da sandunansu suka kuma yi rantsuwa da girman Firʾauna cewa su ne za su yi galaba a kan Annabi Musa. Bayan sun gama duk abin da suka so yi sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya jefa sandarsa sai kawai ta zama macijiya ta riƙa bin ƙarairayinsu na sihiri tana ta haɗiyewa.
Nan take hujjar Annabi Musa ta bayyana, ƙaryar masu sihiri kuma ta ƙare suka gane cewa ba a kan komai suke ba, nan take kuma suka faɗi suna masu sujjada, suka fito fili suka bayyana cewa su sun yi imani da Ubangijin halittu, watau Allah wanda Firʾauna yake musun samuwarsa, shi ne kuma Ubangijin Musa da Harun.
Bayan gaskiya ta bayyana sai Firʾauna ya rikice, ya shiga girman kai yana barazana ga masu sihiri tare da tuhumar su da cewa sun yi imani da Annabi Musa tun kafin ya yi musu izinin hakan. Wannan ya ƙara sa shi ya lalubo wani uzurin da zai faɗa game da imanin masu sihiri, domin ya rufi mutane da shi kada su fahimci gaskiya ce ta bayyana gare su har suka yi imani. Watau Firʾauna ya tuhumi masu sihirin da cewa da ma can Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne shugabansu wanda ya koya musu sihiri, don haka wannan abu da ya faru ba komai ba ne sai haɗin baki a tsakaninsu da shi domin su ƙwace mulkin Masar su fitar da mutanen gari daga garinsu. Don haka sai ya ɗaɗɗana musu mummunar azaba, ta hanyar yanke hannayensu da ƙafafuwansu a tarnaƙe sannan daga baya ya gicciye su a kan kututturan dabino baki ɗayansu, ba zai bar ko da mutum ɗaya daga cikinsu ba.
To amma sai masu sihirin nan suka nuna wa Firʾauna cewa su ba su damu da duk abin da zai yi musu na azaba ba domin sun tabbata su masu komawa ne zuwa ga Ubangijinsu, kuma zai shigar da su cikin rahamarsa madawwamiya.
A ƙarshe suka tabbatar masa da cewa su fatansu Ubangijinsu ya gafarta musu laifukansu da suka yi a baya saboda zamantowarsu farkon waɗanda suka yi imani da Annabi Musa suka gaskata shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yayin da bayi suka zama bayin Allah na gaske masu miƙa wuya ga umarninsa da guje wa haninsa, to lalle zai samar musu mafita daga duk wani rintsi da za su tsinci kansu a cikinsa ta hanyar da ba sa zato.

2. Firʾauna ya aika gari-gari cikin faɗin masarautarsa ta Masar a tattaro masa sojoji domin su yi wa Annabi Musa da Banu-Israʾila ƙofar-rago domin bai san takamaimai inda suka nufa ba yayin fitarsu, bai sani ba ashe shi ne aka yi wa ƙofar-rago don ya hallaka shi da rundunarsa.

3. Babu wani nassi sahihi da ya fayyace adadin Banu-Isra'ila ko adadin rundunar Fir'auna. Duk abin da aka ruwaito game da wannan batu shaci-fadi ne ba ya da wata madogara.

4. Fir'auna ya yi amfani da salon tunzura mutanensa a kan su fito don su bi Annabi Musa da mutanensa su dawo da su ƙasar Masar. Ya nuna musu cewa Annabi Musa da mutanensa wasu 'yan tsirari ne waɗanda bai kamata a ji tsoron su ba. Sannan kuma ya tuna musu cewa Annabi Musa da mutanensa sun yi ta aikata abubuwan da suka fusata mutanen gari domin kuwa sun bijire wa bauta wa abubuwan bautarsu ciki har da shi kansa Fir'auna. Don haka ya zaburar da jama'ar gari a kan su yi shiri domin dawo da Musa da mutanensa, kada su bari su ci gaba da ɓarna da kawo yamutsi da tashin hankali a ƙasa.

5. Idan yaƙini da Allah da yarda da taimakonsa ya cika zuciya, to yakan tafiyar da duk wani tsoro ko fargaba, yana sanya natsuwa da yarda da samun taimako daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da kwantar masa da hankali a kan ya bar damuwa game da ƙaryatawar da Ƙuraishawa suke yi masa duk kuwa da bayyanar ayoyi da mu'ujizoji da dama masu tabbatar da gaskiyar annabcinsa. Allah ya nuna masa cewa ya ba wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) mu'ujizoji masu yawa amma wannan bai hana Fir'auna da mutanensa su ƙaryata shi ba.

Suratus Shu'ara (52-68)

*وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنۡ أَسۡرِ بِعِبَادِيٓ إِنَّكُم مُّتَّبَعُونَ ٥٢ فَأَرۡسَلَ فِرۡعَوۡنُ فِي ٱلۡمَدَآئِنِ حَٰشِرِينَ ٥٣ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَشِرۡذِمَةٞ قَلِيلُونَ ٥٤ وَإِنَّهُمۡ لَنَا لَغَآئِظُونَ ٥٥ وَإِنَّا لَجَمِيعٌ حَٰذِرُونَ ٥٦ فَأَخۡرَجۡنَٰهُم مِّن جَنَّٰتٖ وَعُيُونٖ ٥٧ وَكُنُوزٖ وَمَقَامٖ كَرِيمٖ ٥٨ كَذَٰلِكَۖ وَأَوۡرَثۡنَٰهَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٥٩ فَأَتۡبَعُوهُم مُّشۡرِقِينَ ٦٠ فَلَمَّا تَرَٰٓءَا ٱلۡجَمۡعَانِ قَالَ أَصۡحَٰبُ مُوسَىٰٓ إِنَّا لَمُدۡرَكُونَ ٦١ قَالَ كَلَّآۖ إِنَّ مَعِيَ رَبِّي سَيَهۡدِينِ ٦٢ فَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنِ ٱضۡرِب بِّعَصَاكَ ٱلۡبَحۡرَۖ فَٱنفَلَقَ فَكَانَ كُلُّ فِرۡقٖ كَٱلطَّوۡدِ ٱلۡعَظِيمِ ٦٣ وَأَزۡلَفۡنَا ثَمَّ ٱلۡأٓخَرِينَ ٦٤ وَأَنجَيۡنَا مُوسَىٰ وَمَن مَّعَهُۥٓ أَجۡمَعِينَ ٦٥ ثُمَّ أَغۡرَقۡنَا ٱلۡأٓخَرِينَ ٦٦ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ٦٧ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ٦٨

52. Muka kuma yi wa Musa wahayi cewa: "Ka tafi cikin dare tare da bayina, lalle ku za a biyo bayanku."

53. Sai Fir'auna ya aika zuwa birane don a tattaro (mayaƙa).

54. (Fir'auna yana cewa): "Lalle waɗannan tabbas 'yan tsirarin jama'a ne.

55. "Kuma haƙiƙa su lalle suna fusata mu.

56. "Lalle kuma mu tabbas gaba ɗayanmu masu kwana cikin shiri ne."

57. (Allah Ya ce): Sai Muka fitar da su daga gonaki da kuma idandunan ruwa.

58. Da taskoki da kuma mazauni na alfarma.

59. Kamar haka ne Muka gadar da su ga Banu-Isra'ila.

60. Sai suka bi bayansu a lokacin fitowar rana.

61. To lokacin da jama'ar biyu suka ga juna, sai sahabban Musa suka ce: "Lalle tabbas mu za a cim mana."

62. (Musa) ya ce: “A’a; Ubangijina Yana tare da ni, zai kuwa shiryar da ni (hanyar tsira).”

63. Sai Muka yi wahayi ga Musa cewa: “Ka bugi kogin da sandarka;” (da ya buge shi) sai ya dare, kowanne yanki sai ya zama kamar ƙaton dutse.

64. Muka kuma kusantar da waɗancan (watau mutanen Fir’auna) zuwa can (kusa da kogin).

65. Muka kuma tserar da Musa da waɗanda suke tare da shi gaba ɗaya.

66. Sannan Muka nutsar da sauran mutanen (watau Fir’auna da mutanensa).

67. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu ba su zamanto muminai ba.

68. Kuma lalle Ubangijika tabbas Shi Mabuwayi ne, Mai rahama.

Fir’auna da mutanensa sun ci gaba da kafircinsu, Annabi Musa kuma yana ta nuna musu ayoyi iri-iri, duk sanda ya zo musu da wata aya da ta dame su sai su yi masa alƙawarin cewa idan ya roƙi Allah ya yaye musu ita tabbas za su yi imani da shi kuma lalle za su sakar masa da Banu Isra’ila, sai ko Allah ya yaye musu, sai kuma su karya alƙawarin da suka ɗauka. To bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fitar da ƙaunar za su yi imani da shi ya sakankance da cewa azabar Allah ta riga ta tabbata a kansu, ya kuma fahimci lokacin tserewa tare da Banu Isra’ila ya matso, sai Allah ya yi masa wahayin cewa ya fita cikin dare tare da Banu Isra’ila kuma lalle Fir’auna da rundunarsa za su biyo bayansu, amma idan har sun biyo su da asuba ne to ba za su iya cim masu ba har su isa kogi, daga nan idan sun shiga su kuma sun biyo su a baya sai kogi ya haɗe da su su hallaka.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa yayin da Fir’auna ya ji labarin fitar Annabi Musa da mutanensa daga Masar sai ya aika zuwa biranen Masar domin a tattaro masa da rundunar mayaƙa waɗanda za su bi sawun Annabi Musa da jama’arsa su dawo da su Masar don su ɗandani kuɗarsu. Aka kuwa tara masa rundunarsa ya kuma ƙarfafi gwiwoyinsu da abubuwa uku:
Na farko, ya tabbatar musu da cewa Annabi Musa da mutanensa ‘yan tsiraru ne, don haka dawo da su Masar ba wani abu ne mai wahala ba.
Na biyu, ya nuna musu cewa Annabi Musa da jama’arsa da ma can suna muzguna musu da yawan aikata laifuffuka da hana zaman lafiya a gari, ga shi ma sun gudu da kayan aro da suka karɓa daga hannun mutane.
Na uku, ya nuna musu cewa su kuma da man kullum cikin shiri suke da sanya idanu a kan Annabi Musa da jama’arsa tun al’amarinsu bai yi girma ba har ya zo ya fi ƙarfinsu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya fito da Fir’auna da mutanensa domin su bi sawun Annabi Musa da mutanensa don su hana su fita daga garin Masar, don haka sai suka bar garinsu mai cike da ni’imomi iri-iri, ga gonaki masu cike da shuke-shuke da idanuwan ruwa masu gudana da manya-manyan taskoki cike da dukiya da maka-makan gine-gine na alfarma.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda ya raba Fir’auna da rundunarsa da waɗannan ni’imomi to haka kuma ya gadar wa Banu Isra’ila da wasu ni’imomin irin waɗancan a garuruwan Sham, suka rabu da halin bauta da ƙasƙanci suka koma cikin rayuwa ta jin daɗi da ni’ima da mulki.
Sai Fir’auna da manya-manyan mutanensa da rundunarsa mai ƙarfi da yawa suka yi sammako dab da hudowar rana suka bi bayan Annabi Musa da jama’arsa har sai da suka kusa cim musu, suka fara hango junansu, sai sahabban Annabi Musa suka tsorata suna bayyana cewa lalle fa Fir’auna da mutanensa za su cim musu kuma ga shi ba za su iya tunkarar su da yaƙi ba. Sai Annabi Musa ya kwantar musu da hankali ya tabbatar musu da cewa ba za su iya cim musu ba, domin yana tare da Ubangijinsa, kuma shi ya umarce shi

da ya fito da su cikin dare, don haka yana tare da shi da nasararsa da taimakonsa, kuma zai nuna masa hanyar tsira.
Bayan sun isa dab da Kogin Maliya sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wahayi da cewa ya doki ruwan kogin da sandarsa, nan take kuwa ya doke shi sai suka ga kawai kogin ya tsage ya zama hanyoyi har goma sha biyu, watau adadin ƙabilun Banu-Isra'ila, kowane yanki kuwa na wannan kogi ya zama kamar babban dutse wajen girmansa da tsayuwarsa ta yadda ruwansa ba ya kwarara.
Allah ya bayyana cewa ya kusantar da Fir'auna da mutanensa ga wannan kogin har suka shiga ciki suna tsammanin hanyar wucewa ce. Nan ne fa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da Annabi Musa da Banu Isra'ila da ke tare da shi, babu ko mutum guda cikinsu da ya hallaka a ruwa. Allah kuwa ya hallakar da Fir'auna da mutanensa gaba ɗayansu a cikin kogi suka nutse ko mutum ɗaya bai kai labari ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa cikin wannan abu da ya faru na hallaka Fir'auna da mutanensa da tserar da Annabi Musa da mutanensa akwai aya mai nuna cikakkiyar Ƙudurar Allah da gaskiyar manzancin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), to amma yawancinsu ba sa yin imani ko da sun ga irin waɗannan ayoyi.
Sannan Allah ya bayyana wa Manzonsa cewa lalle Ubangijinsa mabuwayi ne mai damƙar maƙiyansa da azabarsa, kuma mai rahama ne ga duk wanda ya tuba daga cikinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk abin da ba zai iya amsa addu'ar mai addu'a ba, kuma ba zai iya amfanarwa ko cutarwa ba, to bai cancanci a bauta masa ba.

2. Fakewa da bin hanyar iyaye yayin da ake buƙatar hujja wata al'ada ce ta marar hujja.

3. Wanda ya kaɗaita wajen biyan buƙatun halittunsa da maslahohinsu na duniya da na lahira shi ne kaɗai wanda ya cancanta a bauta masa.

4. Bayan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gama isar da saƙon Allah zuwa ga mutanensa ya kirawo su zuwa ga kaɗaita Allah da bauta, wanda hakan kuma ibada ce ga Allah, sai kuma ya shiga roƙon Ubangijinsa buƙatarsa ta duniya da lahira. Abu ne mai kyau mutum ya yi addu'a bayan ya gama aikata wata ibada domin tawassuli da ita a wajen Allah Ta'ala.

5. Annabawa suna bauta wa Allah tare da roƙon sa gidan Aljanna.

6. Lafiyayyar zuciya ita ce wadda ta kuɓuta daga shirka da shakka da son sharri da kafewa a kan bidi'a da zunubbai, ta kuma siffantu da ikhlasi da ilimi da yaƙini da son alheri da ƙaunar Allah da Manzonsa.

Suratus Shu'ara (69-89)
وَٱتۡلُ عَلَيۡهِمۡ نَبَأَ إِبۡرَٰهِيمَ ٦٩ إِذۡ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوۡمِهِۦ مَا تَعۡبُدُونَ ٧٠ قَالُواْ نَعۡبُدُ أَصۡنَامٗا فَنَظَلُّ لَهَا عَٰكِفِينَ ٧١ قَالَ هَلۡ يَسۡمَعُونَكُمۡ إِذۡ تَدۡعُونَ ٧٢
أَوۡ يَنفَعُونَكُمۡ أَوۡ يَضُرُّونَ ٧٣ قَالُواْ بَلۡ وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا كَذَٰلِكَ يَفۡعَلُونَ ٧٤ قَالَ أَفَرَءَيۡتُم مَّا كُنتُمۡ تَعۡبُدُونَ ٧٥ أَنتُمۡ وَءَابَآؤُكُمُ ٱلۡأَقۡدَمُونَ ٧٦
فَإِنَّهُمۡ عَدُوّٞ لِّيٓ إِلَّا رَبَّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٧٧ ٱلَّذِي خَلَقَنِي فَهُوَ يَهۡدِينِ ٧٨ وَٱلَّذِي هُوَ يُطۡعِمُنِي وَيَسۡقِينِ ٧٩ وَإِذَا مَرِضۡتُ فَهُوَ يَشۡفِينِ ٨٠ وَٱلَّذِي يُمِيتُنِي
ثُمَّ يُحۡيِينِ ٨١ وَٱلَّذِيٓ أَطۡمَعُ أَن يَغۡفِرَ لِي خَطِيٓـَٔتِي يَوۡمَ ٱلدِّينِ ٨٢ رَبِّ هَبۡ لِي حُكۡمٗا وَأَلۡحِقۡنِي بِٱلصَّٰلِحِينَ ٨٣ وَٱجۡعَل لِّي لِسَانَ صِدۡقٖ فِي

ٱلۡأٓخِرِينَ ٨٤ وَٱجۡعَلۡنِي مِن وَرَثَةِ جَنَّةِ ٱلنَّعِيمِ ٨٥ وَٱغۡفِرۡ لِأَبِيٓ إِنَّهُۥ كَانَ مِنَ ٱلضَّآلِّينَ ٨٦ وَلَا تُخۡزِنِي يَوۡمَ يُبۡعَثُونَ ٨٧ يَوۡمَ لَا يَنفَعُ مَالٞ وَلَا بَنُونَ ٨٨ إِلَّا مَنۡ أَتَى ٱللَّهَ بِقَلۡبٖ سَلِيمٖ ٨٩

69. Kuma ka karanta musu labarin Ibrahimu?

70. Lokacin da ya ce wa babansa da kuma mutanensa: “Me kuke bauta wa?”

71. Suka ce: “Muna bauta wa gumaka ne, sai mukan duƙufa wajen bautarsu.”

72. (Ibrahimu) ya ce: “Shin suna jin ku kuwa lokacin da kuke kiran su?

73. “Ko kuwa suna amfanar ku ne, ko suna cutarwa?”

74. Suka ce: “A’a; mun sami iyayenmu ne suna aikata kamar haka.”

75. (Ibrahimu) ya ce: “Yanzu kun ga abin nan da kuka kasance kuna bautawa.

76. “Ku da iyayenku da suka gabata.

77. “To lalle su abokan gabata ne sai fa Ubangijin talikai.

78. “Wanda Ya halicce ni, to Shi ne Yake shiryar da ni.

79. “Kuma wanda Shi ne Yake ciyar da ni kuma Yake shayar da ni.

80. “Idan kuma na yi rashin lafiya, to Shi ne zai warkar da ni.

81. “Kuma wanda zai kashe ni sannan Ya (sake) raya ni.

82. “Wanda kuma nake kwaɗayin Ya gafarta min kurakuraina ranar sakamako.

83. “Ubangijina Ka hore min ilimi, kuma Ka haɗa ni da (bayinka) na gari.

84. “Kuma Ka sanya min abin kyakkyawan ambato cikin ‘yan baya.

85. “Kuma Ka sanya ni cikin magada Aljannar ni’ima.

86. “Kuma Ka gafarta wa babana, lalle shi ya zamo cikin ɓatattu.

87. “Kada kuma Ka kunyata ni ranar da za a tashe su.

88. “Ranar da dukiya da ‘ya’yaye ba sa amfani.

89. “Sai dai wanda ya zo wa Allah da lafiyayyar zuciya.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya ba mutanensa labarin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da ya tambayi babansa Azaru da mutanensa cewa, mene ne suke bauta wa wanda ba Allah ba? Sai suka amsa masa da cewa suna bauta wa gumaka ne waɗanda su ne suka sassaƙa su da hannayensu.
Sai Annabi Ibrahimu ya bayyana musu rashin cancantar su bauta musu, ta hanyar tambayarsu cewa shin gumakan nan suna jin su saʾadda suke yin addu'a, kuma suna amsa musu addu'oʾinsu? Ko kuma suna yi musu wani amfani idan sun yi musu ɗaʾa, ko suna cutar da su ne idan sun saɓa musu? To amma su kansu mutanensa sun tabbatar cewa gumakansu ba sa iya yi musu ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa, don haka sai suka rasa wata gamsasshiyar amsa da za su ba shi in ban da cewa su dai haka suka tashi suka sami iyayensu suna irin wannan bautar don haka su kawai sun bi sahun iyayensu ne suna koyi da su wajen bauta musu.
Sai Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ja hankalinsu da cewa, su sani fa duk abubuwan da suke bauta wa su da iyayensu na farko, gaba ɗayansu maƙiyansa ne domin kuwa su ba allolin gaskiya ba ne, sai Allah kaɗai wanda shi ne Ubangijin halittu.
Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da kawo musu siffofin Allah waɗanda da su ne ya cancanci a bauta masa shi kaɗai.
Siffar farko ita ce, shi ne wanda ya halicce shi daga babu ya kuma kyautata halittarsa, kuma shi kaɗai ne yake shiryar da shi ga duk wata masalaharsa ta duniya da ta lahira.
Ta biyu ita ce, shi ne wanda yake ciyar da shi kuma ya shayar da shi. Watau duk arzikin duniya a hannunsa yake babu mai iya hana abin da ya bayar babu kuma mai bayar da abin da ya hana.
Ta uku ita ce, shi ne wanda yake warkar da shi idan ya yi rashin lafiya. Babu wanda waraka take a hannunsa sai Allah shi kaɗai.
Ta huɗu ita ce, shi ne wanda zai karɓi ransa yayin da ajalinsa ya zo. Kuma shi ne wanda zai sake raya shi bayan mutuwarsa. Babu mai iya aikata haka sai shi kaɗai.
Ta biyar ita ce, shi ne wanda yake kwaɗayi ya gafarta masa kurakuransa a ranar sakamako, watau ranar alƙiyama.

An karɓo daga Aʾisha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Na ce: "Ya Manzon Allah, Ibn Judʾan mutum ne da ya kasance a zamanin jahiliyya yana sadar da zumunci, yana kuma ciyar da mabuƙata, shin wannan zai yi masa amfani?" Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ba zai amfane shi ba, domin lalle shi babu wata rana da ya taɓa buɗar bakinsa ya ce: "Ya Ubangijina, ka gafarta min kuskurena a ranar sakamako." [Muslim #214].

Sannan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya duƙufa ga roƙon Allah kan ya yi masa baiwa da abubuwa shida:
Na farko, ya hore masa ilimi na addini domin ya san yadda zai bauta wa Ubangijinsa.
Na biyu, ya sada shi da bayinsa na gari, watau annabawan da suka gabace shi ta hanyar ya sanya shi Aljanna tare da su.
Na uku, ya sanya masa kyakkyawan ambato a cikin alʾummun da za su zo bayansa.
Na huɗu, ya roƙe shi ya sanya shi cikin magada Aljannar niʾima, watau ya shige ta ya more jin daɗin cikinta kamar yadda mai abu yake more abinsa da ya gada ya zama nasa.
Na biyar, ya gafarta wa mahaifinsa Azaru domin ya kasance cikin ɓatattu waɗanda suka rayu a kan bautar gumaka ba Allah ba. Wannan addu'ar ya yi ta ne domin cika wa mahaifinsa alƙawarin da ya yi masa na cewa zai nema masa gafara, amma daga baya ya barranta da shi lokacin da ya tabbatar da cewa shi maƙiyin Allah ne. [Dubi *Suratut Tauba* aya ta 114].
Na shida, kada Allah ya kunyata shi a ranar alƙiyama, ranar da za a tashi kowa da kowa, ranar da dukiya da 'ya'ya ba za su yi amfani ba kamar yadda suke yi wa mai su amfani a nan duniya. Sai dai wanda ya zo wa Allah da lafiyayyar zuciya wadda babu shirka babu riya ko munafurci a cikinta, to wannan shi ne zai amfana da dukiyarsa da ya ciyar domin Allah, da kuma 'ya'yansa da ya bari suka riƙa yi masa kyakkyawar addu'a.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ibrahimu zai haɗu da babansa Azaru ranar alƙiyama fuskarsa ta yi baƙi da ƙura, sai Ibrahimu ya ce masa: "Ban faɗa maka kada ka saɓa mini ba?" Sai babansa ya ce masa: "To a yau ba zan saɓa maka ba." Sai Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ka yi min alƙawari cewa ba za ka wulaƙanta ni ba a ranar da za a tashe su, to wane wulaƙanci ne ya fi na babana wanda aka nesanta shi daga rahama?" Sai Allah Ta'ala ya ce: "Lalle ni na haramta wa kafirai shiga Aljanna." Sannan sai a ce masa: "Ya Ibrahimu, mene ne a ƙarƙashin ƙafafunka?" Sai ya duba sai kawai ya ga wani kure kaca-kaca da jini, sai a kama ƙafafunsa (watau kuren) sai a jefa shi cikin wuta." [Bukhari #3350].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A ranar hisabi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai matso wa da 'yan Aljanna gidajensu kusa da su tun ma kafin su shige ta, domin gaggauto musu da farin cikinsu da nutsuwa. Su ma 'yan wuta a ranar alƙiyama za a bijiro musu da wutarsu tun kafin a jefa su cikinta, don gaggauto musu da azabarsu da tashin hankalinsu.

2. Don ɓatattun mutane sun ɗora alhakin ɓatansu a kan shugabanninsu waɗanda suka ɓatar da su, wannan ba zai amfana musu komai ba.

3. Tabbatar da jayayyar mabiya 'yan wuta da shugabanninsu a cikin wutar ranar da za su gane cewa shugabannin nasu da suka ɓatar da su, ba za su amfana musu komai ba a wurin Allah, hasali ma ga shi an tara su baki ɗaya a cikin wutar Jahannama.

4. Iblis yana da rundunarsa daga cikin aljannu da mutane. Su ne masu fafutikar ingiza mutane zuwa ga saɓon Allah, kamar yaɗa shirka da zalunci da munafunci da zinace-zinace da cin riba da fitsara da sauransu.

5. Tabbatar da cewa kafiri ba shi da rabo a cikin ceton masu ceto.

6. Waɗanda Allah ya riga ya ƙaddara musu ɓata da taɓewa, duk wani wa'azi da duk wata aya ba za ta amfane su ba.

Suratus Shu'ara (90-104)

وَأُزْلِفَتِ ٱلْجَنَّةُ لِلْمُتَّقِينَ ﴿٩٠﴾ وَبُرِّزَتِ ٱلْجَحِيمُ لِلْغَاوِينَ ﴿٩١﴾ وَقِيلَ لَهُمْ أَيْنَ مَا كُنتُمْ تَعْبُدُونَ ﴿٩٢﴾ مِن دُونِ ٱللَّهِ هَلْ يَنصُرُونَكُمْ أَوْ يَنتَصِرُونَ ﴿٩٣﴾
فَكُبْكِبُواْ فِيهَا هُمْ وَٱلْغَاوُۥنَ ﴿٩٤﴾ وَجُنُودُ إِبْلِيسَ أَجْمَعُونَ ﴿٩٥﴾ قَالُواْ وَهُمْ فِيهَا يَخْتَصِمُونَ ﴿٩٦﴾ تَٱللَّهِ إِن كُنَّا لَفِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٩٧﴾ إِذْ نُسَوِّيكُم بِرَبِّ
ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٩٨﴾ وَمَآ أَضَلَّنَآ إِلَّا ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿٩٩﴾ فَمَا لَنَا مِن شَٰفِعِينَ ﴿١٠٠﴾ وَلَا صَدِيقٍ حَمِيمٍ ﴿١٠١﴾ فَلَوْ أَنَّ لَنَا كَرَّةً فَنَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١٠٢﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ
لَءَايَةً ۖ وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٠٣﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٠٤﴾

90. Aka kuma kusantar da Aljanna ga masu taƙawa.

91. Kuma aka bayyanar da (wutar) Jahima ga ɓatattu.

92. Aka kuma ce da su: "Ina abubuwan da kuka kasance kuna bauta wa?

93. "Waɗanda ba Allah ba? Shin za su taimake ku, ko za su taimaki kansu?"

94. Sai aka kikkifa su cikinta (wutar) su da ɓatattu.

95. Da kuma rundunar Iblis gaba ɗaya.

96. Sai suka ce, alhali suna jayayya da juna a cikinta:

97. "Mun rantse da Allah tabbas mun kasance (a duniya) cikin ɓata bayyananne.

98. "Lokacin da muke daidaita ku da Ubangijin talikai.

99. "Ba kuwa waɗanda suka ɓatar da mu sai manyan masu laifuka.

100. "To a (yau) ba mu da wasu masu ceto.

101. "Ba kuma wani aboki na ƙut-da-ƙut.

102. "To ina ma da za mu samu damar komawa, sai mu zamanto daga muminai!"

103. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu, ba su zamanto muminai ba.

104. Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon bayinsa a ranar alƙiyama masu taƙawa da kuma kafirai. Za a kusanto da Aljanna ga masu kiyaye dokokin Ubangijinsu, suna aikata abin da ya umarce su suna kuma barin abin da ya hana su. Ita kuma wutar Jahannama a bayyanar da ita ga ɓatattu waɗanda suka bijire wa addinin gaskiya a duniya. Sai a tambaye su ina gumakan da suka zamanto suna bauta wa a duniya ba Allah ba? Shin za su taimake su a wannan mawuyacin hali da suke ciki, ko kuma za su taimaki kansu? Ba za su iya ko ɗaya ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa a lokacin za a jefa su cikin wutar Jahannama su da waɗanda suka ɓatar da su wasu kan wasu tare da rundunar Iblis, watau shaiɗanun mutane da aljannu.
Daga nan sai jayayya ta kaure tsakanin mushrikai da waɗanda suka bautar da su a duniya, su riƙa rantsuwa cewa wallahi da ma su sun kasance cikin ɓata lokacin da suke daidaita su da Ubangijin halittu, suka riƙa bautar su kamar yadda ake bauta wa Allah. Kuma ba wasu ne suka ɓatar da su ba sai shaiɗanun shuwagabanninsu waɗanda suka ja su zuwa ga bautar wanin Allah. A lokacin ne za su tabbatar da cewa, ba su da wasu masu ceton su daga azabar Allah, kuma ba su da wani aboki amini wanda zai kare su daga azabar Allah ko ya cece su. Daga nan sai su shiga nadama da da-na-sanin cewa ina ma da za su sake samun damar komawa duniya da sun zamo muminai, to amma ina, bakin alƙalami ya riga ya bushe.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a cikin wannan labari da ya gabata da wannan faɗakarwa da ta biyo baya, lallai akwai abin izina da waʾazi ga masu waʾazantuwa, sai dai kuma yawancinsu ba su zamo masu yin imani ba. Sai kuma ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa Ubangijinsa mabuwayi ne, zai azabtar da maƙiyansa, mai rahama ne kuma ga waɗanda suka tuba daga cikinsu suka koma gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya ƙaryata manzo ɗaya to ya ƙaryata dukkan manzanni ne, domin saƙon da suka zo da shi daga Allah iri ɗaya ne, shi ne bautar Allah shi kaɗai ba tare da abokin tarayya ba.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana aiko manzanni daga cikin nasabar mutanensu domin kada su ji ƙyashin yin imani da su, sannan kuma sun san su ciki da waje ba sai sun yi wani bincike a kansu ba.

3. Kasancewarsa manzo ne zuwa gare su su kaɗai wata ni'ima ce da martaba a gare su da ya wajaba su yi wa Allah godiya a kanta.

4. Bayanin rashin halaccin karɓar wani lada a kan isar da saƙon Allah da bayanin shari'arsa.

5. Waɗanda suka riga yin imani da karɓar gaskiya su ne manya masu daraja a wurin Allah; ƙasƙantattu kuwa su ne waɗanda suka kafirce wa Allah suka ƙaryata annabawansa.

6. Ba ya halatta a kori wani daga majalisin ilimi saboda talaucinsa ko don masu wadata ba sa ƙaunar ganin sa a wurin.

Suratus Shu'ara (105-122)

كَذَّبَتْ قَوْمُ نُوحٍ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٠٥﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ نُوحٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٠٦﴾ إِنِّى لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٠٧﴾ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٠٨﴾ وَمَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ
مِنْ أَجْرٍ ۖ إِنْ أَجْرِىَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَـٰلَمِينَ ﴿١٠٩﴾ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١١٠﴾ *قَالُوٓاْ أَنُؤْمِنُ لَكَ وَٱتَّبَعَكَ ٱلْأَرْذَلُونَ ﴿١١١﴾ قَالَ وَمَا عِلْمِى بِمَا كَانُواْ
يَعْمَلُونَ ﴿١١٢﴾ إِنْ حِسَابُهُمْ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّى ۖ لَوْ تَشْعُرُونَ ﴿١١٣﴾ وَمَآ أَنَا۠ بِطَارِدِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١١٤﴾ إِنْ أَنَا۠ إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿١١٥﴾ قَالُواْ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ يَـٰنُوحُ لَتَكُونَنَّ
مِنَ ٱلْمَرْجُومِينَ ﴿١١٦﴾ قَالَ رَبِّ إِنَّ قَوْمِى كَذَّبُونِ ﴿١١٧﴾ فَٱفْتَحْ بَيْنِى وَبَيْنَهُمْ فَتْحًا وَنَجِّنِى وَمَن مَّعِىَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿١١٨﴾ فَأَنجَيْنَـٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ فِى ٱلْفُلْكِ
ٱلْمَشْحُونِ ﴿١١٩﴾ ثُمَّ أَغْرَقْنَا بَعْدُ ٱلْبَاقِينَ ﴿١٢٠﴾ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَةً ۖ وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٢١﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٢٢﴾

105. Mutanen Nuhu sun ƙaryata mazanni.

106. Lokacin da ɗan'uwansu Nuhu ya ce da su: "Yanzu ba za ku kiyaye dokokin Allah ba?

107. "Lalle ni Manzo ne amintacce a gare ku.

108. "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni.

109. "Ba na kuma tambayar ku wani lada a game da shi (isar da manzancin). Ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai.

110. "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni."

111. Suka ce: "Yanzu ma yi imani da kai alhali ƙasƙantattu ne mabiyanka?"

112. Ya ce: "Ba ni da sani game da abin da suka zamanto suna aikatawa.

113. "Hisabinsu kawai yana wajen Ubangijina ne; da za ku gane.

114. "Ni kuma ba mai korar muminai ba ne.

115. "Ni kawai mai gargaɗi ne mai bayyanawa."

116. Suka ce: “Ya Nuhu, mun rantse idan ba ka daina (faɗar abin da kake faɗa) ba, tabbas za ka zamanto daga cikin jefaffu!”

117. Ya ce: “Ya Ubangijina, lalle mutanena sun ƙaryata ni.

118. “Ka yi hukunci tsakanina da su, kuma Ka tserar da ni tare da muminan da suke tare da ni.”

119. Sai Muka tserar da shi da waɗanda suke tare da shi a cikin jirgin ruwan da ke maƙare (da mutane da dabbobi).

120. Sannan bayan haka Muka nutsar da sauran.

121. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu ba su zamanto muminai ba.

122. Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa labarin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa mutanensa sun ƙaryata manzannin Allah, saboda sun ƙaryata Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Domin abin da ya zo musu da shi na kaɗaita Allah irinsa ne sauran manzannin Allah suka zo da shi. Annabi Nuhu ya gargaɗe su da cewa su ji tsoron Allah ta hanyar barin bautar gumaka, su bauta wa Allah shi kaɗai, kuma shi Manzon Allah ne da ya aiko zuwa gare su kuma mai amana ne ba zai ƙara komai a kan abin da aka yi masa wahayinsa ba, ba kuma zai rage wani abu ba. Ya sake nanata musu gargaɗin su kiyaye dokokin Allah su aikata abin da ya umarce su su kuma guji abin da ya hana su, kuma su yi masa ɗa'a shi kansa, domin zamantowarsa manzo zuwa gare su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tabbatar wa da mutanensa cewa ba ya neman wani lada a wurinsu a kan isar musu da saƙon Ubangijinsu balle ma su ga cewa ya ɗora musu wani nauyi da ba za su iya ɗauka ba. Ya faɗa musu cewa shi ladansa yana wurin Allah ne kawai wanda shi ne Ubangijin halittu duka.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Nuhu ya yi ta nanata wa mutanensa cewa su ji tsoron Allah, su kiyaye dokokinsa, su kuma yi masa biyayya, tare da tabbatar musu da hujjojinsa masu nuna gaskiyar manzancinsa da amanarsa da nasiharsa gare su, amma sai mutanensa suka bijire, suka zo da wani dalilin da yake ƙunshe da wauta da rashin hankali da cewa ta yaya za su yi imani da shi su karɓi abin da ya zo musu da shi, alhalin mabiyansa ƙasƙantattun mutane ne, ba ya tare da wasu manyan mutane masu daraja.
Sai Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya mayar musu da martani da cewa shi ba shi da wata masaniya game da abin da waɗannan mutane suke aikatawa, watau ba a umarce shi da ya binciki kowa ba kafin ya karɓi imaninsu. Abin da ya sani dai shi ne, sakamakon kowa yana ga Allah wanda shi ne ya san abin da suka ɓoye da abin da suka bayyana a sarari. Da sun gane wannan da ba za su faɗa masa abin da suka faɗa masa ba.
To yayin da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fahimci cewa mutanensa suna neman sa ne da ya kori mabiyansa waɗanda suke ganin ƙasƙantattu ne idan har yana son su yi imani da shi, sai ya shaida musu cewa shi ba zai kori muminai daga majalisarsa ba, domin ba abin da suka yi masa da zai sa ya kore su. Shi kawai mai gargaɗi ne a fili mai tsoratar da mutane azabar Allah da fushinsa, don haka babu batun korar wani a hannunsa.
Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) dai bai sassauta ba; ya ci gaba da wa'azinsa da nasiharsa ga mutanensa ba dare ba rana tsawon lokaci, su kuma sai ƙara bijire masa suke yi. A ƙarshe ma suka fito fili suka fara yi masa barazana da cewa lalle idan bai daina yi musu wannan wa'azi ba to za su jefe shi da duwatsu har mutuwa.

To da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ga kafircin mutanensa ya ƙara tsananta sai ya koma ga Ubangiji ya ɗaga hannu ya roƙe shi yana shaida masa cewa mutanensa fa sun ƙaryata shi, ba shi da sauran wata dabara, yana roƙon sa da ya yi hukunci tsakaninsa da mutanensa, ya hallaka su saboda kafewarsu a kan kafirci, shi kuma ya tserar da shi tare da muminai waɗanda suka yi imani da shi.
Sai ko Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karɓi addu'arsa ya tserar da shi har da muminan da suke tare da shi a cikin jirgin ruwa wanda yake cike da mutane da dabbobi. Sannan ya hallaka sauran mutanensa ta hanyar nutsar da su cikin ruwan Ɗufana.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yin hannunka-mai-sanda da cewa, lalle a cikin wannan labarin na Annabi Nuhu da tserar da shi da hallakar da mutanensa tabbas akwai abin izina ga mutane masu ɗaukar izina. To amma yawancinsu ba sa yin imani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa cewa shi mabuwayi ne yana kuma yin uƙuba ga maƙiyansa, kuma mai rahama ne ga duk wanda ya tuba daga cikinsu ya koma ga Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Manzannin Allah masu amana ne game da saƙon da Allah ya aiko su da shi.

2. Ba ya halatta a biya mai wa'azi a kan wa'azinsa da isar da saƙon Allah.

3. Ba ya dacewa ga mumini ya riƙa almubazzaranci yana gina abubuwan da ba za su amfane shi ba.

4. Tsoratarwa da azabar Allah da gargaɗi a kan saɓa masa, yana daga cikin hanyoyin annabawa na da'awa.

5. Munin fakewa da biyayya ga iyaye wajen saɓon Allah da kauce wa gaskiya.

Suratus Shu'ara (123-140)

كَذَّبَتْ عَادٌ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٢٣﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ هُودٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٢٤﴾ إِنِّى لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٢٥﴾ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٢٦﴾ وَمَآ
أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ ۖ إِنْ أَجْرِىَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَـٰلَمِينَ ﴿١٢٧﴾ أَتَبْنُونَ بِكُلِّ رِيعٍ ءَايَةً تَعْبَثُونَ ﴿١٢٨﴾ وَتَتَّخِذُونَ مَصَانِعَ لَعَلَّكُمْ
تَخْلُدُونَ ﴿١٢٩﴾ وَإِذَا بَطَشْتُم بَطَشْتُمْ جَبَّارِينَ ﴿١٣٠﴾ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٣١﴾ وَٱتَّقُوا۟ ٱلَّذِىٓ أَمَدَّكُم بِمَا تَعْلَمُونَ ﴿١٣٢﴾ أَمَدَّكُم
بِأَنْعَـٰمٍ وَبَنِينَ ﴿١٣٣﴾ وَجَنَّـٰتٍ وَعُيُونٍ ﴿١٣٤﴾ إِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿١٣٥﴾ قَالُوا۟ سَوَآءٌ عَلَيْنَآ أَوَعَظْتَ أَمْ لَمْ تَكُن
مِّنَ ٱلْوَٰعِظِينَ ﴿١٣٦﴾ إِنْ هَـٰذَآ إِلَّا خُلُقُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿١٣٧﴾ وَمَا نَحْنُ بِمُعَذَّبِينَ ﴿١٣٨﴾ فَكَذَّبُوهُ فَأَهْلَكْنَـٰهُمْ ۗ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَـَٔايَةً ۖ وَمَا كَانَ
أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٣٩﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٤٠﴾

123. Adawa (ma) sun ƙaryata manzanni.

124. Lokacin da ɗan'uwansu Hudu ya ce da su: "Yanzu ba kwa riƙa kiyaye dokokin (Allah) ba?

125. "Lalle ni Manzo ne amintacce gare ku.

126. "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni.

127. "Kuma ba na tambayar ku wani lada game da shi (isar da manzancin); ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai.

128. “Yanzu kwa riƙa yin dogayen gine-gine a kan tuddai kuna sharholiya?

129. “Kuma ku riƙa gina ganuwoyi da maka-makan gidaje kamar za ku dawwama?

130. “Idan kuma kuka yi damƙa sai kukan yi damƙa da tsanani.

131. “To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni.

132. “Kuma ku kiyaye dokokin (Allah) wanda Ya ni’imta ku da abin da kuka sani.

133. “Ya ni’imta ku da dabbobin ni’ima da ‘ya’ya.

134. “Da kuma gonakai da idanuwan ruwa.

135. “Lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wani yini mai girma.”

136. Suka ce: “Mu duk ɗaya ne a wajenmu; ko ka yi wa’azi ko kuwa kada ka zamanto daga masu wa’azi.

137. “Wannan ba wani abu ba ne in ban da halayyar mutanen farko.

138. “Mu kuma ba waɗanda za a yi wa azaba ba ne.”

139. Sai suka ƙaryata shi, sannan Muka hallaka su. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu ba su zamanto muminai ba.

140. Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabi (ﷺ) labarin Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da cewa Adawa sun ƙaryata manzanni lokacin da suka ƙaryata Annabi Hudu, yayin da yake yi musu wa’azi yana nuna musu cewa, me ya sa ba za su ji tsoron Allah ba su bar bauta wa gumaka ba Allah ba? Ya bayyana musu cewa shi manzon Allah ne da ya aiko shi zuwa gare su kuma mai amana ne ba zai ƙara wani abu a cikin saƙon Allah ba kuma ba zai rage komai ba. Sai kuma ya umarce su da su kiyaye dokokin Allah, su aikata abin da ya umarce su da aikatawa su guji abin da ya hana su, kuma su yi masa ɗa’a, domin kasancewarsa Manzon Allah ne zuwa gare su. Kuma ya tabbatar musu da cewa ba ya buƙatar wani lada daga wajensu a kan saƙon da yake isar musu daga Allah, ladansa kawai yana wurin Allah Ubangijin talikai ne.
Sannan Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tsawata wa mutanensa game da abin da suke ciki na shagalta da rayuwar duniya wadda ta sa ba sa son maganar lahira, ya kuma ja hankalinsu game da manya-manyan gine-gine da suke yi a wurare maɗaukaka domin sharholiya da wasanni kawai ba tare da wani amfani na duniya ko lahira ba. Kuma suna gina ganuwowi da maka-makan gidaje kamar za su dawwama a duniya ba za su mutu ba. Idan kuma za su kai wani farmaki na kisa ko duka to sukan wuce iyaka ne su kai shi da tsattsaurar zuciya wadda babu rahama ko tausayi a cikinta.
Sai Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sake umartar su da su kiyaye dokokin Allah; su yi aiki da umarninsa su kuma guje wa haninsa, kuma su yi masa biyayya a kan abin da yake umartar su da shi. Ya ƙara jan hankalinsu a kan su ji tsoron Allah su kiyayi fushinsa, shi ne fa ya ni’imta su da abubuwan jin daɗi na rayuwa, ya ba su dabbobin ni’ima da ‘ya’ya maza da kuma gonaki da idanuwan ruwa masu kwarara. Ya ƙara da cewa yana jiye musu tsoron azabar wani yini mai girma, watau ranar alƙiyama.

Bayan duk wannan wa'azin da Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mutanensa da tsoratar da su ranar alƙiyama, amma sai suka bayyana masa cewa duk ɗaya ne a wajensu ya yi musu wa'azi ko kada ya yi, su dai ba za su yi imani da shi ba, ba kuma za su bar abin da suke a kai ba. Abin da suke a kai ba wani sabon abu ne ba, in ban da addinin mutanen farko, watau na iyayensu da kakanninsu kuma shi ne al'adarsu, don haka suna nan a kan bin tafarkin iyayensu, kuma sun tabbatar ba za a azabtar da su a kan haka ba.
Sai Allah ya bayyana cewa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ci gaba da ƙaryata shi, sai Allah ya hallakar da su da wata iska mai tsanani.
Allah ya bayyana cewa a cikin wannan hallakawar da ya yi musu akwai abin izina ga masu ɗaukar izina, to amma yawancinsu ba masu yin imani ne ba.
Ya kuma tabbatar wa Manzonsa cewa shi ne mabuwayi mai iya kama maƙiyansa duk sa'adda ya ga dama, mai rahama ne kuma ga waɗanda suka tuba suka koma gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saƙon manzanni duka iri ɗaya ne, don haka ƙaryata ɗaya daga cikinsu ƙaryata su ne baki ɗaya.

2. Riƙon amana wani take ne ga dukkan manzanni da masu kira zuwa ga Allah da sauran mutane na gari, a kowane zamani kuma a kowane wuri.

3. Tuna wa mutane ni'imar da Allah ya yi musu domin su riƙa ambaton sa suna gode masa suna kuma yi masa biyayya.

4. Gargaɗi da kashedi game da biyayya ga maɓarnata masu yaɗa saɓon Allah a bayan ƙasa ba sa son gyara sam-sam.

5. Tabbatar da cewa saɓon Allah ɓarna ce a bayan ƙasa.

6. Bayani a kan cewa sihiri wata mummunar al'ada ce daɗaɗɗiya a rayuwar ɗan'adam.

7. Don an samar wa da wani manzo mu'ujiza wannan ba ya nufin dole ne mutanensa su yi imani da shi.

8. Idan azabar Allah ta zo gadan-gadan duk wata nadama ba ta da wani amfani.

Suratus Shu'ara (141-159)
كَذَّبَتۡ ثَمُودُ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٤١ إِذۡ قَالَ لَهُمۡ أَخُوهُمۡ صَٰلِحٌ أَلَا تَتَّقُونَ ١٤٢ إِنِّي لَكُمۡ رَسُولٌ أَمِينٞ ١٤٣ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٤٤ وَمَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ مِنۡ أَجۡرٍۖ إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٤٥ أَتُتۡرَكُونَ فِي مَا هَٰهُنَآ ءَامِنِينَ ١٤٦ فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٖ ١٤٧ وَزُرُوعٖ وَنَخۡلٖ طَلۡعُهَا هَضِيمٞ ١٤٨ وَتَنۡحِتُونَ مِنَ ٱلۡجِبَالِ بُيُوتٗا فَٰرِهِينَ ١٤٩ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٥٠ وَلَا تُطِيعُوٓاْ أَمۡرَ ٱلۡمُسۡرِفِينَ ١٥١ ٱلَّذِينَ يُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا يُصۡلِحُونَ ١٥٢ قَالُوٓاْ إِنَّمَآ أَنتَ مِنَ ٱلۡمُسَحَّرِينَ ١٥٣ مَآ أَنتَ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُنَا فَأۡتِ بِـَٔايَةٍ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ١٥٤ قَالَ هَٰذِهِۦ نَاقَةٞ لَّهَا شِرۡبٞ وَلَكُمۡ شِرۡبُ يَوۡمٖ مَّعۡلُومٖ ١٥٥ وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوٓءٖ فَيَأۡخُذَكُمۡ عَذَابُ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ١٥٦ فَعَقَرُوهَا فَأَصۡبَحُواْ نَٰدِمِينَ ١٥٧ فَأَخَذَهُمُ ٱلۡعَذَابُۗ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ١٥٨ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ١٥٩

141. Samudawa sun ƙaryata manzanni.

142. Lokacin da ɗan'uwansu Salihu ya ce da su: "Yanzu ba kwa yi taƙawa ba?

143. "Lalle ni Manzo ne amintacce gare ku.

144. "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni.

145. "Kuma ba na tambayar ku wani lada game da shi (isar da manzancin); ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai.

146. "Yanzu (zatonku) za a bar ku ne cikin abin da yake a nan (duniya) cikin kwanciyar hankali?

147. "(Watau) a cikin gonaki da idandunan ruwa?

148. "Da shuke-shuke da dabinai masu taushin 'ya'ya?

149. "Kuma kuna fafe duwatsu kuna yin gidaje kuna masu nuna ƙwarewa?

150. "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni.

151. "Kada kuma ku bi umarnin maɓarnata.

152. "Waɗanda suke ɓarna a bayan ƙasa, kuma ba sa gyara."

153. Suka ce: "Lalle kai kana daga waɗanda aka sihirce ne kawai.

154. "Kai ba kowa ba ne sai mutum kamarmu, to ka zo mana da aya idan ka kasance daga masu gaskiya."

155. (Salihu) ya ce: "Wannan taguwa ce, tana da (ranar) shanta ku ma kuna da rana sananniya ta shanku.

156. "Kada kuwa ku shafe ta da mugun abu, sai azabar wani yini mai girma ta kama ku."

157. Sai suka soke ta, sai kuwa suka wayi gari suna masu nadama.

158. Sai azaba ta kama su. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; kuma yawancinsu ba su zamanto muminai ba.

159. Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabi (ﷺ) labarin Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da ya aike shi zuwa ga ƙabilarsa Samudawa da cewa sun ƙaryata manzanni saboda sun ƙaryata Annabinsu Salihu wanda ya zo musu da irin saƙon da duk manzannin Allah suka zo da shi na kaɗaita Allah da bauta. Ɗan'uwansu Annabi Salihu ya faɗa musu cewa me ya sa ba za su kiyaye dokokin Allah, su bi umarninsa su guje wa haninsa ba? Ya kuma tabbatar musu cewa shi Manzon Allah ne zuwa gare su kuma mai amana ne ba zai ƙara komai a cikin saƙon da Allah ya yi masa wahayinsa ba, ba kuma zai rage wani abu ba. Shi kuma ba ya neman wani lada a wurinsu na isar musu da saƙon Allah ballantana su ji cewa ya ɗora musu wani harajin da ya fi ƙarfinsu, domin shi ladansa yana wurin Allah Ubangijin talikai, shi kaɗai ne zai biya shi.

Sai kuma ya gargaɗe su tare da yi musu waʾazi a kan irin rayuwar da suke yi ta sheƙe-aya; kar su zaci cewa za a bar su cikin niʾimar da suke mora a nan duniya hankalinsu a kwance, a ƙyale su su ci gaba da rayuwa ta jin daɗi a cikin gonaki da idanuwan ruwa masu gudana da shuke-shuke iri-iri da dabinai masu nunannun ʻyaʾya. Sannan su ci gaba da fafe duwatsu suna yin gidajen zama tare da nuna ƙwarewarsu wajen gina su.
Ya kuma sake umartar su da su kiyaye dokokin Allah, su bi umarninsa su guji haninsa, sannan su yi masa ɗaʾa cikin duk abin da zai umarcesu ko kuma ya hana su, su guji bin umarnin masu ƙetare iyakokin Allah da aikata laifuffuka da yaɗa ɓarna a bayan ƙasa, ba sa ƙoƙarin yin gyara ko kaɗan.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mutanen Annabi Salihu sun yi watsi da duk wani waʾazi da ya yi musu; maimakon su yi imani da shi sai ma suka shiga tuhumar sa da cewa yana cikin mutanen da ake yi wa sihiri a kai-a kai har sihirin ya kawar musu da hankulansu, don haka ba za su yarda da maganganunsa ba.
Haka kuma sun soke shi da cewa ai shi mutum ne kamarsu babu abin da ya fi su da shi ballantana har a ba shi manzanci su ba a ba su ba. Kuma idan har da gaske shi Manzon Allah ne to ya nuna musu wata alama da za ta nuna shi mai gaskiya ne. Sai ko Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hore masa taguwa a matsayin muʾujiza gare shi domin tabbatar da annabcinsa.
Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana musu cewa wannan taguwar tana da ranar shan ruwanta su ma mutanen gari suna da ƙayyadajjiyar ranar shan su, don haka kada su shiga ranarta, ita ma ba za ta shiga tasu ranar ba. Ya kuma gargaɗe su da kada su kuskura su shafe ta da wani mugun abu, kamar duka ko kisa sai a dalilin haka wata azaba ta auka musu ta hallaka su.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mutanen Annabi Salihu saboda ƙeta da tsaurin kai suka haɗa baki a kan su soke wannan taguwar, sai ko mafi tsagerancin cikinsu ya soke ta. A kan wannan sai suka wayi gari suna nadama bisa ga aika-aikarsu yayin da azabar Allah ta aukar musu. Nadama a lokacin kuwa ba ta yi amfani ba. Azabar kuwa ita ce tsawa da girgizar ƙasa wadda ta hallaka su gaba ɗaya. Allah ya bayyana cewa lalle a game da labarin Annabi Salihu da mutanensa akwai abin izina da darasi ga masu ɗaukar izina da darasi, to amma kuma yawancin mutane ba sa yin imani ko da kuwa an nuna musu ayoyi da muʾujizoji masu yawa.
Allah kuma ya bayyana wa Manzonsa cewa shi mabuwayi ne mai azabtar da maƙiyansa, kuma mai rahama ne, yana kuma karɓar tuban wanda ya tuba ya koma gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ƙaryata manzo ɗaya daidai yake da ƙaryata dukkanin manzanni, saboda saƙo iri ɗaya suka zo da shi na kaɗaita Allah da bauta.

2. Amana siffa ce tabbatacciya ga duk wani manzo da Allah ya aiko.

3. Hanyar tsira ɗaya rak ga jamaʾa ko mutum guda, ita ce tsoron Allah da biyayya ga Allah da Manzonsa.

4. Mafi girman aikin alfasha a duniya shi ne shaʾawa ta neman maza.

5. Wajibi ne mumini ya ƙyamaci mummunan aiki a zuciyarsa ko ba zai iya hanawa da hannunsa ko harshensa ba.

6. Duk saʾadda ɓarna ta yawaita a gari to a jira zuwan uƙubar Allah matuƙar ba a fito an yanke ta ba, masu yin ta sun tuba zuwa ga Allah.

7. Duk girman muʾujiza da Allah zai ba wa wani manzo ba lalle ne mutanensa su yi imani da shi ba.

Suratus Shu'ara (160-175)

كَذَّبَتْ قَوْمُ لُوطٍ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٦٠﴾ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ لُوطٌ أَلَا تَتَّقُونَ ﴿١٦١﴾ إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ﴿١٦٢﴾ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ﴿١٦٣﴾ وَمَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍۖ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٦٤﴾ أَتَأْتُونَ ٱلذُّكْرَانَ مِنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٦٥﴾ وَتَذَرُونَ مَا خَلَقَ لَكُمْ رَبُّكُم مِّنْ أَزْوَٰجِكُمْۚ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ عَادُونَ ﴿١٦٦﴾ قَالُواْ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ يَٰلُوطُ لَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُخْرَجِينَ ﴿١٦٧﴾ قَالَ إِنِّي لِعَمَلِكُم مِّنَ ٱلْقَالِينَ ﴿١٦٨﴾ رَبِّ نَجِّنِي وَأَهْلِي مِمَّا يَعْمَلُونَ ﴿١٦٩﴾ فَنَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥٓ أَجْمَعِينَ ﴿١٧٠﴾ إِلَّا عَجُوزًا فِي ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿١٧١﴾ ثُمَّ دَمَّرْنَا ٱلْـَٔاخَرِينَ ﴿١٧٢﴾ وَأَمْطَرْنَا عَلَيْهِم مَّطَرًاۖ فَسَآءَ مَطَرُ ٱلْمُنذَرِينَ ﴿١٧٣﴾ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَةًۖ وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم مُّؤْمِنِينَ ﴿١٧٤﴾ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿١٧٥﴾

160. Mutanen Ludu sun ƙaryata manzanni.

161. Lokacin da ɗan'uwansu Ludu ya ce da su: "Yanzu ba kwa kiyaye dokokin Allah ba?

162. "Lalle ni Manzo ne amintacce gare ku.

163. "To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni.

164. "Kuma ba na tambayar ku wani lada game da shi (isar da manzancin); ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai.

165. "Yanzu kwa riƙa zaike wa maza daga halittu?

166. "Kuma ku bar abin da Ubangijinku Ya halitta na matanku dominku? A'a, ku dai mutane ne masu ƙetare iyaka."

167. Suka ce: "Tabbas Ludu idan ba ka bar (faɗar abin da kake faɗa ba) haƙiƙa za ka kasance daga korarru (daga garin nan)."

168. (Ludu) ya ce: "Lalle ni ina cikin masu ƙyamar aikin nan naku.

169. "Ya Ubangijina, Ka tserar da ni da iyalina daga (sakamakon) abin da suke aikatawa."

170. Sai Muka tserar da shi da iyalinsa gaba ɗaya.

171. Sai fa wata tsohuwa (watau matarsa) da ta (kasance tana) cikin hallakakku.

172. Sannan Muka hallaka sauran.

173. Muka kuma saukar musu da ruwa na azaba; to ruwan azabar waɗanda aka yi wa gargaɗi ya munana.

174. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; yawancinsu kuwa ba su zamanto muminai ba.

175. Kuma lalle Ubangiijnka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa (ﷺ) labarin Annabi Ludu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa, lokacin da ya aike shi gare su, sai suka ƙaryata manzanni ta hanyar ƙaryata shi, domin duk manzannin Allah saƙo iri ɗaya suka zo da shi, watau Tauhidi. Allah ya

bayyana cewa, ɗan'uwansu Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ja hankalinsu a kan su kiyaye dokokin Allah, watau su bi umarninsa su guje wa haninsa su bar aikata shirka. Ya tabbatar musu cewa shi Manzo ne da Allah ya aiko musu kuma mai amana ne, ba zai ƙara komai cikin saƙon da aka yi masa wahayi ba, ba kuma zai rage komai ba. Sannan kamar sauran manzannin da suka gabace shi ya shaida wa mutanensa cewa ba ya neman wani lada daga wajensu a kan isar musu da saƙon Allah da ya yi ballantana har su ce ya ɗora musu nauyin da ya fi ƙarfinsu. Shi kawai ladansa yana wurin Allah, shi ne zai biya shi ba wani ba.
Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo ya sami mutanensa suna aikata wata mummunar alfasha, watau saduwa da maza ta duburarsu, ya nuna musu girman laifinsu, kuma don me suke barin matansu da Allah ya halatta musu domin su biya buƙatar sha'awarsu a wajensu? Annabi Luɗu ya tabbatar musu da cewa lalle su mutane ne da suke ƙetare iyaka.
To amma sai mutanensa suka yi watsi da wannan kiran har ta kai suna yi masa barazanar sai sun kore shi daga shi har mabiyansa daga ƙasarsu idan har bai daina yi musu wa'azi a kan wannan batu ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yayin da Annabi Luɗu ya ga mutanensa sun kafe a kan ci gaba da wannan mummunan aiki nasu sai ya bayyana musu cewa lalle shi yana ƙyamar wannan aiki nasu. Ya kuma ɗaga hannu ya yi addu'a yana mai roƙon Allah ya tserar da shi tare da iyalansa daga azabar da za ta auka wa waɗannan maɓarnata saboda mummunan aikinsu. Sai Allah ya amsa addu'arsa ya kuma tserar da shi tare da iyalansa in ban da matarsa wadda take kafira, ita kam tana cikin halakakku. Bayan Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fita daga alƙaryar Sadum tare da iyalansa sai Allah ya hallaka sauran mutanensa mummunar hallakarwa, watau ya yi musu ruwan duwatsu daga sama. Sai Allah ya tabbatar da cewa wannan ruwan azaba ya munana ƙwarai ga mutanen da suka jima ana yi musu gargaɗi ana tsoratar da su azabar Allah amma suka bijire suka ƙi yin imani.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lalle a cikin wannan labari na Annabi Luɗu da azabar da ya saukar wa mutanensa akwai izina da wa'azi ga mutanen da suke ɗaukar izina. Sai dai yawancinsu ba su zama masu yin imani ba duk kuwa da ayoyin Allah da suka gani.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar wa Manzonsa cewa shi mabuwayi ne mai azabtar da maƙiyansa, mai rahama ne kuma ga waɗanda suka tuba suka koma gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni da taƙawa aiki ne wajibi a kan duk wani mai kira zuwa ga Allah.

2. Ba daidai ne ga mai wa'azi ya nemi a biya shi ladan wa'azinsa ba, domin yin haka zai sa mutane su guji sauraron wa'azinsa.

3. Wajabcin cika mudu da daidaita sikeli da haramcin tauye wa mutane haƙƙinsu.

4. Haramcin yaɗa ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar aikata saɓon Allah da zaluntar mutane.

5. Kafirai da yawa sun fake da cewa kasancewar manzonsu mutum ne shi ya hana su yin imani da shi, yayin da kuma wasu suke ƙyamar a ce Manzon Allah (ﷺ) mutum ne kamar sauran mutane sai dai Allah ya zaɓe shi ya yi masa wahayi. Matsayin waɗannan mutane na da da na yanzu duka babban kuskure ne da rashin sanin al'adar Allah wajen aiko da manzanni.

Suratus Shu’ara (176-191)

كَذَّبَ أَصۡحَٰبُ لۡـَٔيۡكَةِ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٧٦ إِذۡ قَالَ لَهُمۡ شُعَيۡبٌ أَلَا تَتَّقُونَ ١٧٧ إِنِّي لَكُمۡ رَسُولٌ أَمِينٞ ١٧٨ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٧٩ وَمَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ
مِنۡ أَجۡرٍۖ إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٨٠ *أَوۡفُواْ ٱلۡكَيۡلَ وَلَا تَكُونُواْ مِنَ ٱلۡمُخۡسِرِينَ ١٨١ وَزِنُواْ بِٱلۡقِسۡطَاسِ ٱلۡمُسۡتَقِيمِ ١٨٢ وَلَا تَبۡخَسُواْ
ٱلنَّاسَ أَشۡيَآءَهُمۡ وَلَا تَعۡثَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُفۡسِدِينَ ١٨٣ وَٱتَّقُواْ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ وَٱلۡجِبِلَّةَ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٨٤ قَالُوٓاْ إِنَّمَآ أَنتَ مِنَ ٱلۡمُسَحَّرِينَ ١٨٥ وَمَآ أَنتَ
إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُنَا وَإِن نَّظُنُّكَ لَمِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ١٨٦ فَأَسۡقِطۡ عَلَيۡنَا كِسَفٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ١٨٧ قَالَ رَبِّيٓ أَعۡلَمُ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٨٨
فَكَذَّبُوهُ فَأَخَذَهُمۡ عَذَابُ يَوۡمِ ٱلظُّلَّةِۚ إِنَّهُۥ كَانَ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٍ ١٨٩ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ١٩٠ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ
ٱلرَّحِيمُ ١٩١

176. Mutanen kurmi sun ƙaryata manzanni.

177. Lokacin da Shu’aibu ya ce da su: “Yanzu ba kwa kiyaye dokokin (Allah) ba?

178. “Lalle ni Manzo ne amintacce gare ku.

179. “To ku kiyaye dokokin Allah kuma ku bi ni.

180. “Kuma ba na tambayar ku wani lada game da shi (isar da manzancin); ladana yana wajen Ubangijin talikai kawai.

181. “Ku cika mudu kada kuma ku zamanto daga masu tauye (shi).

182. “Kuma ku riƙa yin awon nauyi da ma’auni na adalci.

183. “Kada kuma ku tauye wa mutane kayayyakinsu, kuma kada ku yawaita ɓarna a bayan ƙasa.

184. “Kuma ku kiyaye dokokin (Allah) wanda Ya halicce ku da kuma al’ummu na farko.”

185. Suka ce: “Kai dai kana daga waɗanda aka sihirce ne kawai.

186. “Kuma kai ba kowa ba ne sai mutum kamarmu, kuma ma lalle muna zaton kana daga maƙaryata!

187. “Sai ka jeho mana da yankuna (na azaba) daga sama in ka kasance daga masu gaskiya!”

188. (Shu’aibu) Ya ce: “Ubangijina Ya fi kowa sanin abin da kuke aikatawa.”

189. Sai suka ƙaryata shi, sannan sai azabar yinin girgije (na wuta) ta kama su. Lalle ta kasance azabar wani yini ne mai girma.

190. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya; sai dai kuma yawancinsu ba su kasance muminai ba.

191. Kuma lalle Ubangijinka tabbas Shi ne Mabuwayi, Mai rahama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba wa Manzonsa (ﷺ) labaran annabawa. A nan ya ba shi labarin Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya aike shi zuwa ga

mutanen wata alƙarya mai yawan bishiyoyi kusa da Madyana, ya gargaɗe su da cewa me ya hana su su kiyaye dokokin Allah, watau su bi umarninsa su kuma guji haninsa? Ya tabbatar musu da cewa shi Manzon Allah ne da ya aiko shi zuwa gare su, shi kuma mai amana ne ba zai ƙara ko ya rage wani abu cikin wahayin da Allah ya yi masa ba. Ya sake umartar su da su kiyaye dokokin Allah; su bi umarninsa su guji haninsa, shi kuma su yi masa ɗa'a cikin abin da yake faɗa musu.
Ya kuma tabbatar musu cewa shi ba ya neman wani lada daga wajensu a kan isar musu da saƙon Allah da shari'arsa ballantana ma su yi zaton cewa ya ɗora musu wani haraji wanda ya fi ƙarfinsu. Don haka ladansa yana wurin Allah Ubangijin halittu ne kawai.
Mutanen Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) duk da shirkarsu suna kuma tauye mudun awo da sikeli, don haka sai ya umarce su da cewa idan za su sayar wa da mutane kayansu to su cika musu mudu kada su tauye wa mutane mudunsu. Idan kuma awon kayan nauyi ne za su yi wa mutane to su yi musu da sikeli madaidaici. Haka kuma ya hana su tauye wa mutane haƙƙinsu na awon mudu ko na sikeli. Ya kuma hana su yawaita ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar saɓon Allah da bijire wa dokokinsa.
Kuma lallai su ji tsoron Allah; su aikata umarninsa su guje wa haninsa, Allah shi ne wanda ya halicce su har da al'ummun da suka gabata.
To amma sai mutanen Annabi Shu'aibu suka bijire wa wa'azinsa, suka ma tuhumce shi da cewa ana ta yi masa sihiri ne a kai-a kai har hankalinsa ya taɓu, don haka ne yake yi musu irin waɗannan maganganu. Sannan suka nuna masa cewa shi fa bai fi su da komai ba da har Allah zai zaɓe shi ya ba shi manzanci, domin kuwa shi mutum ne kamarsu. Ƙarshe ma suka ce babban zaton da suke yi masa shi maƙaryaci ne yana yi musu ƙaryar manzanci ne, don haka ba za su yi imani da shi ba. Suka ma neme shi da ya jeho musu wani yanki na azaba daga sama idan har da gaske ne shi Manzon Allah ne.
Sai Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya mayar musu da martani da cewa Ubangijinsa ya fi kowa sanin laifukan da suke aikatawa na shirka da saɓon Allah da cutar mutane, don haka shi ne zai yanke musu hukuncin saukar musu da azaba idan ya ga dama ya gaggauto musu ita, idan kuma ya ga dama ya saurara musu zuwa wani lokaci na daban.
Sai suka ci gaba da ƙaryata Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), a ƙarshe sai wata azaba mai girma ta auka musu, yayin da wani girgije ya yi musu rumfa ya lulluɓe su bayan wani yini mai tsananin zafi, sai aka yi musu ruwan wuta ta ƙone su gaba ɗaya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lalle ranar hallakar da su wata babbar rana ce mai cike da ban tsoro.
Allah ya bayyana cewa lalle a cikin labarin Annabi Shu'aibu da mutanensa da hallakarsu akwai abin izina ga mutane masu ɗaukar izina, amma yawancinsu ba sa yin imani.
Ya kuma tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa shi mabuwayi ne ya fi ƙarfin maƙiyansa, kuma mai rahama ne yana karɓar tuban wanda ya tuba ya komo gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne wanda yake sauko wa da Manzon Allah wahayi daga Allah.

2. Mala'ikun Allah masu amana ne a kan duk wani saƙo da za a aiko su da shi, ba sa ƙarawa ba kuma sa ragewa.

3. Tabbatar da annabtar Manzon Allah (ﷺ).

4. Tabbatar da tsarewar da Allah ya yi wa Alƙur'ani, domin ya saukar da shi a bisa zuciyar Manzon Allah (ﷺ), shi kuma ya kiyaye shi matuƙar kiyayewa, sannan ya isar da shi ga al'ummarsa.

5. Alƙur'ani Balaraben littafi ne, don haka fahimtar sa yadda ya kamata ba za ta yiwu ba sai da fahimtar harshen Larabci yadda ya kamata.

6. Sanin shari'ar Allah da ilimin addinin Musulunci ba zai yi zurfi ba sai ta hanyar sanin harshen Larabci, domin mafi girman madogara ta fahimtar Musulunci ita ce Alƙur'ani wanda shi kuma Balaraben littafi ne.

7. Kafa wa mushirikai hujja a kan gaskiyar Alƙur'ani ta hanyar tabbatar da shaidar wasu masu adalci daga cikin ma'abota littafi a kan cewa Alƙur'ani littafin Allah ne daga gare shi yake.

8. Kafirai yayin da za su ga azaba za su yi burin su tuba amma ba za su sami damar tuba ba.

9. Neman gaggauto da azabar Allah babbar wauta ce da rashin hankali.

10. Ni'imomin da kafirai suke ciki da arzikin duniya ba ya nufin Allah ya karrama su ne, a'a talala ce yake yi musu.

11. Bayanin sunnar Allah ta tabbatar da cewa ba ya hallaka al'umma saboda laifinta har sai ya aika mata da masu gargaɗi.

12. Tsarkake Alƙur'ani daga kusantar shaiɗanu zuwa gare shi.

Suratus Shu'ara (192-212)

وَإِنَّهُۥ لَتَنزِيلُ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٩٢ نَزَلَ بِهِ ٱلرُّوحُ ٱلۡأَمِينُ ١٩٣ عَلَىٰ قَلۡبِكَ لِتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُنذِرِينَ ١٩٤ بِلِسَانٍ عَرَبِيّٖ مُّبِينٖ ١٩٥ وَإِنَّهُۥ لَفِي زُبُرِ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٩٦
أَوَ لَمۡ يَكُن لَّهُمۡ ءَايَةً أَن يَعۡلَمَهُۥ عُلَمَٰٓؤُاْ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ١٩٧ وَلَوۡ نَزَّلۡنَٰهُ عَلَىٰ بَعۡضِ ٱلۡأَعۡجَمِينَ ١٩٨ فَقَرَأَهُۥ عَلَيۡهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ مُؤۡمِنِينَ ١٩٩ كَذَٰلِكَ
سَلَكۡنَٰهُ فِي قُلُوبِ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٢٠٠ لَا يُؤۡمِنُونَ بِهِۦ حَتَّىٰ يَرَوُاْ ٱلۡعَذَابَ ٱلۡأَلِيمَ ٢٠١ فَيَأۡتِيَهُم بَغۡتَةٗ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٢٠٢ فَيَقُولُواْ هَلۡ نَحۡنُ مُنظَرُونَ ٢٠٣
أَفَبِعَذَابِنَا يَسۡتَعۡجِلُونَ ٢٠٤ أَفَرَءَيۡتَ إِن مَّتَّعۡنَٰهُمۡ سِنِينَ ٢٠٥ ثُمَّ جَآءَهُم مَّا كَانُواْ يُوعَدُونَ ٢٠٦ مَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يُمَتَّعُونَ ٢٠٧ وَمَآ أَهۡلَكۡنَا مِن
قَرۡيَةٍ إِلَّا لَهَا مُنذِرُونَ ٢٠٨ ذِكۡرَىٰ وَمَا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ٢٠٩ وَمَا تَنَزَّلَتۡ بِهِ ٱلشَّيَٰطِينُ ٢١٠ وَمَا يَنۢبَغِي لَهُمۡ وَمَا يَسۡتَطِيعُونَ ٢١١ إِنَّهُمۡ عَنِ ٱلسَّمۡعِ
لَمَعۡزُولُونَ ٢١٢

192. Kuma lalle shi (Alƙur'ani) saukarwa ce ta Ubangijin talikai.

193. Ruhi amintacce (watau Jibrilu) ne ya sauko da shi.

194. A bisa zuciyarka don ka zamanto daga masu gargaɗi.

195. (Ya saukar da shi) da harshen Larabci mabayyani.

196. Kuma lalle shi yana daga cikin littattafan farko.

197. Yanzu bai ishe su aya ba cewa, malaman Banu- Isra'ila sun san shi?

198. Da kuwa Mun saukar da shi ga wani wanda ba Balarabe ba.

199. Sannan ya karanta musu shi, to da ba za su yi imani da shi ba.

200. Kamar haka ne Muka shigar da shi (ƙaryata Annabi) cikin zukatan manyan masu laifi.

201. Ba za su yi imani da shi ba har sai sun ga azaba mai raɗaɗî.

202. Sannan (azabar) za ta zo musu ba zato ba tsammani, ba tare da suna sane ba.

203. Sai su ce: "Yanzu za a saurara mana?"

204. Yanzu azabarmu suke neman gaggautowa?

205. Ka ba Ni labari idan Muka jiyar da su daɗî na tsawon shekaru.

206. Sannan kuma abin da ake yi musu alkawarin narko da shi ya zo musu.

207. Abin da ake jiyar da su daɗî a da ba zai amfana musu komai ba.

208. Ba Mu taɓa hallaka wata al'umma ba face sai ta samu masu yi mata gargaɗî.

209. (Wannan) tunatarwa ce (gare su), ba Mu kuwa kasance azzalumai ba.

210. Kuma shaiɗanu ba su sauko da shi ba.

211. Kuma bai kamace su ba, ba kuma za su iya ba.

212. Lalle su ababen kangewa ne daga jin (wahayi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana matsayin littafin da ya saukar wa Annabi (ﷺ), da cewa shi Alƙur'ani ne saukakke daga Allah Ubangijin talikai wanda Mala'ika Jibrilu amintaccen Allah ya saukar da shi a bisa zuciyar Manzon Allah (ﷺ) don ya zama ɗaya daga cikin manzannin Allah waɗanda suke gargaɗin mutane suna tsoratar da su azabar Allah. Kuma ya saukar da shi da harshen Larabci bayyananne, don haka Larabawa ba su da wata hujjar ƙaryata shi domin suna fahimtar komai a cikinsa dalla-dalla.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa a cikin littattafan annabawan farko ma an ambaci Alƙur'ani domin dukkansu sun yi albishir da shi. Ya ƙara da cewa, yanzu mushirikai masu ƙaryata Manzon Allah bai isa aya gare su mai tabbatar da gaskiyarsa ba cewa malaman Banu-Isra'ila ma sun san haƙiƙanin abin da Allah ya saukar wa Manzonsa kamar irin su Abdullahi ɗan Salam (Allah ya ƙara masa yarda) da Salmanul Farisi (Allah ya ƙara masa yarda)?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin tsaurin kan Ƙuraishawa wajen rashin yin imani da Alƙur'ani, da cewa da a ce ya saukar da shi ga wani mutum Ba'ajame wanda ba ya jin harshen Larabci, ya kuma zo ya karanta musu shi da Larabcinsa mai cike da fasaha al'amarin da zai ba wa kowa mamaki, to tabbas ba za su yi imani da cewa daga Allah yake ba, domin tsananin taurin kansu da ƙin gaskiya.
Hakanan da a ce za a saukar da Alƙur'ani da harshen wani wanda ba ya iya magana da Larabci ya karanta musu shi, to a nan ma da sai su ce su fa ba sa fahimtar harshensa, don haka tunda ba sa gane komai daga wannan Alƙur'ani, sai su ƙi yin imani da shi su ƙi gaskata shi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kamar yadda za su ƙaryata wancan mutumin Ba'ajame, to hakanan Allah ya shigar da ƙaryata Alƙur'ani da kafirci cikin zukatan kafirai, ba za su taɓa canzawa su bar wannan kafircin nasu ba, kuma ba za su yi imani ba har sai sun ga azaba mai raɗaɗî wadda za ta zo

musu ba zato ba tsammani. To a lokacin ne za su tsinci kawunansu cikin tsananin nadama har su riƙa cewa, shin ko za a saurara musu zuwa wani lokaci su tuba zuwa ga Allah?
Kafirai sun nace da tambayar Manzon Allah (ﷺ) wai yaushe ne azabar Allah da ake tsoratar da su da ita za ta zo musu? Shi kuma sai ya yi mamaki da cewa yanzu azabar Allah suke neman gaggautowa? Kai wasu ma daga cikinsu suna ƙalubalantar sa da cewa ba za su yi imani da shi ba har sai ya kifo musu da wani yanki na azaba daga sama, alhali kuwa suna da labarin yadda Allah ya hallaka al'ummun da suka gabata.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa tsawon rai ba ya hana aukuwar azaba ga wanda ya jawo wa kansa ita. Ya faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa duk wani tsawon rai da za a jiyar da kafirai dadî da shi komai yawansu sai alƙawarin da aka yi musu na azabar Allah ya zo musu, to wane amfani wannan jin dadî na duniya zai yi musu? Daga ranar da suka bar duniya ya yanke kenan, sannan wata azaba mai ɗorewa za ta auka musu.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "A ranar alƙiyama za a kawo wanda ya fi kowa jin dadî a duniya daga cikin 'yan wuta sai a tsoma shi cikin wuta sau ɗaya sai a ce masa, ' ya kai ɗan'adam, shin ka taɓa haɗuwa da alheri tunda kake? Shin ka taɓa jin dadîn wata ni'ima tunda Allah ya yi ka? ' Sai ya ce: "A'a, wallahi ya Ubangijina." Sai kuma a zo da wanda ya fi kowa shan wahala a duniya daga cikin 'yan Aljanna, sai a tsoma shi a Aljanna sau ɗaya, sai a ce masa, ' ya kai ɗan'adam, shin tunda kake ka taɓa shan wahala? Ka taɓa shiga wani tsanani? ' Sai ya ce: "A'a, wallahi ya Ubangijina ban taɓa shiga wata wahala ba tunda nake." [Muslim #2807].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa babu wata al'umma da ya hallakar cikin al'ummun da suka gabata har sai da ya aiko musu da manzanni suka yi musu gargaɗî da wa'azi ya saukar musu da littattafai waɗanda suka ƙunshi shiriya da karantarwa, domin shi Allah ba azzalumi ne ba ballantana ya hallaka su gabanin ya gargaɗe su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da martani ga mushirikai masu cewa wai Annabi Muhammadu (ﷺ) boka ne, kuma Alƙur'ani da yake karanta musu sheɗanu ne suke sauko masa da shi. Allah ya ƙaryata su da cewa ba sheɗanu ne suka saukar masa da shi ba, kuma ma wannan aiki bai dace da sheɗanu ba kuma ba za su iya yin haka ba, domin an riga an katange su a sama ba za su iya sauraron wani wahayi ba ballantana su jiyo shi su kawo wa Annabi (ﷺ).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman lamarin Tauhidi da haɗarin shirka da Allah, domin sababi ne na haɗuwa da azabar Allah.

2. Muhimmancin fara da'awa ta kan makusanta saboda girman haƙƙinsu.

3. Muhimmancin tausasawa da bin komai a sannu ga mai da'awa zuwa ga Allah domin hakan yana da matuƙar tasiri a da'awarsa.

4. Koyi da halayen Manzon Allah (ﷺ) da kyawawan ɗabi'unsa abu ne mai matuƙar muhimmanci da tasiri wajen tabbatar da maslahohi na duniya da lahira.

5. Wajabcin nesanta kai daga shirka da saɓon Allah.

6. Babban abin da zai taimaki mumini a kan aikinsa na kira zuwa ga Allah da sauran al'amuran rayuwarsa shi ne dogaro ga Allah da neman tallafinsa, domin shi babu abin da yake gagarar sa kuma mai tausayi ne ga bayinsa.

7. Tsayawa gaba ga Allah cikin salla da yawan sujjada babbar hanya ce ta samun kusanci da Allah da neman dafawarsa da agajinsa ga bawansa.

Suratus Shu'ara (213-220)
فَلَا تَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُعَذَّبِينَ ٢١٣ وَأَنذِرۡ عَشِيرَتَكَ ٱلۡأَقۡرَبِينَ ٢١٤ وَٱخۡفِضۡ جَنَاحَكَ لِمَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٢١٥ فَإِنۡ عَصَوۡكَ فَقُلۡ إِنِّي بَرِيٓءٞ مِّمَّا تَعۡمَلُونَ ٢١٦ وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱلۡعَزِيزِ ٱلرَّحِيمِ ٢١٧ ٱلَّذِي يَرَىٰكَ حِينَ تَقُومُ ٢١٨ وَتَقَلُّبَكَ فِي ٱلسَّٰجِدِينَ ٢١٩ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٢٢٠

213. To kada ka bauta wa wani tare da Allah, sai ka zamanto daga waɗanda za a yi wa azaba.
214. Kuma ka gargaɗi danginka mafiya kusanci.

215. Ka kuma tausasa ga wanda ya bi ka daga muminai.

216. To idan suka saɓa maka sai ka ce: "Ni lalle ba ruwana da abin da kuke aikatawa."

217. Ka kuma dogara ga Mabuwayi, Mai rahama.

218. Wanda Yake ganin ka yayin da kake tashi (don yin salla).

219. Da kuma (yayin) jujjuyawarka cikin masu sujjada.

220. Haƙiƙa Shi Mai ji ne, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana bautar wani abin bauta tare da shi; duk kuwa wanda ya aikata haka to sai Allah ya yi masa azaba.
Sai kuma ya umarci Manzon Allah (ﷺ) da ya gargaɗi danginsa na kusa domin kada azabar Allah ta same su idan har suka mutu suna shirka.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Yayin da wannan ayar ta sauka: "Kuma ka gargaɗi danginka na kurkusa", sai Manzon Allah (ﷺ) ya fita ya hau kan Dutsen Safa ya ɗaga muryarsa ya ce: "Ku yi shiri gari ya waye." Sai suka ce: "Wane ne wannan yake ihu?" Sai suka ce: "Muhammadu ne." Sai suka taru a gabansa sai ya ce: "Ya Bani wane, ya Bani wane, ya Bani wane, ya Bani Abdi Manafi, ya Bani Abdilmuɗɗalib." Sai duk suka taru a wajen sai ya ce: "Ku ba ni labari, da zan faɗa muku cewa ga wasu mayaƙa nan za su fito muku ta bayan wannan dutsen shin za ku gaskata ni?" Sai suka ce: "Ba mu taɓa samun ka da ƙarya ba." Sai ya ce: "To ni lalle mai gargaɗi ne gare ku da wata azaba mai tsanani a nan gaba." Sai Abu Lahab ya ce: "Tir da kai, yanzu don wannan kawai ka tara mu?" Sai ya tashi ya yi tafiyarsa, sai surar *Tabbat Yada Abi Lahabin* ta sauka." [Bukhari #4770 da Muslim #208].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya tausasa magana ko aiki ga muminai waɗanda suka bi shi domin tausaya musu da nuna jin ƙai gare su.
Sai kuma ya umarce shi da cewa idan mutanensa suka saɓa masa, suka bijire wa abin da ya zo musu da shi na kaɗaita Allah da yi masa ɗa'a, to ya tabbatar musu da cewa shi ba ruwansa da duk abin da suke aikatawa na shirka da saɓon Allah, aikinsa kawai shi ne ya yi musu wa'azi da nasiha kuma ya yi musu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya dogara da shi cikin dukkan al'amuransa domin shi ne Mabuwayi mai yin uƙuba ga maƙiyansa, mai kuma rahama ga duk wanda ya tuba ya koma gare shi. Shi ne kuma wanda yake ganin sa lokacin da yake tsayawa yana salla, yana kuma jujjuyawa daga wani

yanayi zuwa wani yanayi a cikin masallata; yana sane da ɗaukacin ayyukansa da sauran ayyukan bayinsa, domin shi mai ji ne kuma masani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ƙaryata da'awar kafirai ta cewa Alƙur'ani ya yi kama da abin da bokaye suke faɗa.

2. Ƙaryata maganar Ƙuraishawa ta cewa Annabi (ﷺ) boka ne ko mawaƙi.

3. Bayani a kan cewa sheɗanu na aljannu suna ƙulla alaƙa da sheɗanu na mutane wajen shuka ƙarairayi da yaɗa saɓon Allah.

4. Bayani a kan cewa mabiyan miyagun mawaƙa a kowane wuri su ne ɓatattu kuma lalatattun mutane a kowane zamani.

5. Waƙa akwai wadda take mai kyau akwai kuma mummuna.

Suratus Shu'ara (221-227)

هَلۡ أُنَبِّئُكُمۡ عَلَىٰ مَن تَنَزَّلُ ٱلشَّيَٰطِينُ ٢٢١ تَنَزَّلُ عَلَىٰ كُلِّ أَفَّاكٍ أَثِيمٖ ٢٢٢ يُلۡقُونَ ٱلسَّمۡعَ وَأَكۡثَرُهُمۡ كَٰذِبُونَ ٢٢٣ وَٱلشُّعَرَآءُ يَتَّبِعُهُمُ ٱلۡغَاوُۥنَ ٢٢٤
أَلَمۡ تَرَ أَنَّهُمۡ فِي كُلِّ وَادٖ يَهِيمُونَ ٢٢٥ وَأَنَّهُمۡ يَقُولُونَ مَا لَا يَفۡعَلُونَ ٢٢٦ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَذَكَرُواْ ٱللَّهَ كَثِيرٗا وَٱنتَصَرُواْ مِنۢ
بَعۡدِ مَا ظُلِمُواْۚ وَسَيَعۡلَمُ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ أَيَّ مُنقَلَبٖ يَنقَلِبُونَ ٢٢٧

221. Shin ba Na ba ku labari ba game da wanda sheɗanu suke saukar masa?

222. Suna sauka ne a kan duk wani maƙaryaci mai yawan laifi.

223. Suna jefa wa (bokaye) abin da suka sato jinsa, yawancinsu kuwa maƙaryata ne.

224. Mawaƙa kuwa ɓatattu ne suke bin su.

225. Ba ka ga cewa su kutsawa suke yi cikin kowanne kwari ba?

226. Lalle kuma suna faɗar abin da ba sa aikatawa.

227. Sai dai waɗanda suka yi imani kuma suka yi aiki na gari, kuma suka ambaci Allah da yawa, suka kuma yi sakayya bayan an zalunce su. Waɗanda suka yi zalunci kuwa ba da daɗewa ba za su san kowace makomar za su koma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana mayar da martani ne ga kafirai masu cewa sheɗanu ne suka saukar wa da Annabi (ﷺ) Alƙur'ani. Allah ya bayyana musu haƙiƙanin waɗanda sheɗanu suke saukar musu da cewa, sheɗanu suna sauka ne ga duk wani maƙaryaci mai yawan saɓa wa Allah, kamar bokaye da danginsu. Sheɗanu suna hawa sama ta kusa su sato musu jin abin da mala'iku suke tattaunawa a junansu, sai su jefa wa abokansu bokaye abin da suka sato sauraronsa. Allah kuma ya bayyana cewa yawancin bokaye maƙaryata ne, ko da kuwa za su faɗi gaskiya ɗaya to za su gauraya ta da ƙarya ɗari.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan Allah ya zartar da wani al'amari a sama sai mala'iku su buga fukafukansu domin nuna ƙasƙantar da kai ga maganar Allah, sai wani ƙara ya fita kamar an buga sarƙa a kan falalen dutse, har sai an yaye tsoro daga zukatansu sai su ce: "Me Ubangijinku ya ce?" Sai su amsa wa mai wannan tambayar da cewa: "Gaskiya ya faɗa, shi kuma Maɗaukaki ne Mai girma." Sai masu satar magana su saci wannan maganar. Su kuwa waɗannan sheɗanun sukan hau junansu ne, wasu kan wasu, sai na sama ya kasa kunne ya sato maganar sai ya jefa ta ga na ƙasa da shi, shi ma kuma sai ya jefa wa na ƙasa da shi, haka har ta zo ga matsafi ko boka. Tana yiwuwa tauraro mai wuta ya same shi kafin ya kai ta ga na ƙasa da shi, yana kuma yiwuwa ya jefa maganar kafin tauraron ya cim masa. Sai boka ya gauraya wannan gaskiyar ɗaya da ƙarya ɗari, sai a riƙa cewa, ba a rana kaza ya taɓa faɗar kaza da kaza ba (watau wannan abu kuma ya faru)? Sai a gaskata shi a dalilin wannan kalmar da aka jiyo masa daga sama." [Bukhari #4800].

Sannan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da martani ga masu kiran Annabi (ﷺ) da mawaƙi har suna iƙirarin cewa abin da ya zo da shi waƙa ce. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mawaƙa, ɓatattu ne suke bin su waɗanda suka kauce wa gaskiya, su ne suke ruwaito waƙoƙinsu ƙarya da gaskiya, Allah ya bayyana irin yadda mawaƙa suke kutsawa cikin kowanne kwazazzabo na waƙe-waƙe, wani lokaci ta hanyar yabo, wani lokaci kuwa ta hanyar zambo, wani lokaci kuma ta hanyar alfahari, wani lokaci kuma ta hanyar habaici, su faɗi ƙarya da gaskiya. Allah ya siffanta su da cewa suna faɗin abin da ba sa aikatawa, su ingiza mutane su yi kyauta su kuma ba sa yi, su kuma nuna a guji rowa su kuma ita suka kama; su ce a yi gaskiya su kuma suna faɗar ƙarya.
Amma kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi togaciya ta wasu mawaƙan da suka siffantu da siffofi huɗu: Masu imani da Allah; masu aiki nigari; masu ambaton Allah da yawa; da kuma waɗanda suka yi sakayya ga maƙiya Allah bayan sun zalunce su.
Waɗannan mawaƙa su ne irin su Hassan ɗan Sabit (Allah ya ƙara masa yarda) da Abdullahi ɗan Rawaha (Allah ya ƙara masa yarda) da Ka'abu ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda).
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗanda suka yi zalunci ta hanyar shirka da saɓon Allah da cutar da jama'a, da sannu za su san irin makomarsu a ranar lahira, ranar da Allah zai yi wa kowa hisabi a kan aikinsa mai kyau da marar kyau.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman Alƙur'ani.

2. Bayani a kan cewa ayoyin Alƙur'ani su ne mafi ɗaukakar ayoyi kuma bayanansu a fili suke. Suna kuma ɗauke da bayanin manya-manyan manufofi na shari'a da kyawawan ayyuka da ɗabi'u.

3. Masu imani su ne kaɗai masu shiryuwa da ayoyin Alƙur'ani.

4. Imani yana tare da abin da yake tabbatar da shi a zahiri, kamar tsai da salla da fitar da zakka da yin imani da ranar lahira wanda yake haifar da ayyuka na gari.

27-Suratun Namli

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ta fi shahara da sunan *Suratun Namli*, watau surar tururuwa; saboda a cikinta ne Allah ya ba da labarin tururuwa da Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Wasu sun kira ta da sunan *Suratul Hudhud*, watau surar alhudhudu, saboda labarin da yake cikinta na alhuduhudu. Da akwai wasu sunayen ma na daban.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Da yawa daga cikin malamai sun ambaci cewa an yi ijima'i a kan wannan Sura *Makkiyya* ce, watau an saukar da ita gabanin hijira.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba'in da takwas (48) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, kuma ta sauka bayan *Suratus Shu'ara*' gabanin *Suratul Kasas*, kamar yadda aka ruwaito daga Abdullahi ɗan Abbas da almajirinsa Sa'idu ɗan Jubairu.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta tis'in da uku (93) ne a lissafin mutanen Kufa. Amma a lissafin malaman Basra da Sham adadinsu tis'in da huɗu (94) ne. A kuma lissafin mutanen Makka da Madina adadinsu tis'in da biyar (95) ne.

5. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne magana a kan imani da Allah da bauta masa shi kaɗai, da imani da ranar lahira da imani da wahayi da tabbatar da cewa babu wanda ya san gaibu sai Allah.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
- Nuni zuwa ga girman Alƙur'ani da mu'ujizarsa.
- Jan hankali ta hanyar ba da labarin wani ƙasaitaccen mulki da Allah ya ba wa Annabi Dawuda da Annabi Sulaimanu, irin mulkin da bai taɓa ba wa wani ɗan'adam ba.
- Jan hankali ta hanyar kawo labarin wata al'umma ta Larabawa da Allah ya ba su ƙarfin mulki, watau al'ummar Samudawa. Sannan da wani ƙasaitaccen mulki da ya ba wa Larabawa a wani lokaci a tarihi, watau mulkin Saba'i.
- Jayayya da mushirikai don bayyana ɓacin addininsu da ƙaryar bautar da suke yi wa gumaka ba Allah ba.
- Tabbatar da ranar alƙiyama da abin da ta ƙunsa na ban tsoro da alamominta.

Namli (1-3)

طسٓ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡقُرۡءَانِ وَكِتَابٖ مُّبِينٖ ١ هُدٗى وَبُشۡرَىٰ لِلۡمُؤۡمِنِينَ ٢ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ يُوقِنُونَ ٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ṬA SIN. Waɗannan ayoyin Alƙur'ani ne kuma Littafi mabayyani.
2. (Kuma) shiriya da albishir ne ga muminai.
3. Waɗanda suke tsai da salla, suke kuma ba da zakka suna masu sakankancewa da ranar lahira.

Surar ta buɗe da wasu haruffa waɗanda muka yi bayanin irinsu a baya. (Dubi *Suratul Bakara*, aya ta (1). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan ayoyi ne da ya saukar na Alƙur'ani wanda shi kuma littafi ne bayyananne babu wata rikitarwa a cikinsa. Duk wanda ya tsaya ya karance shi cikin tsanaki, to zai fahimci lallai daga Allah yake.

Sai ya bayyana cewa masu shiryuwa da ayoyin Alƙur'ani su ne muminai waɗanda suka yi imani da Allah. A gare su ayoyin Alƙur'ani shiriya ne da albishir da samun sakamakon Ubangijinsu Allah, watau gidan Aljanna. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasu muhimman siffofi na waɗannan muminan guda uku.
Ta ɗaya, tsayar da salla, watau yin ta kamar yadda aka yi umarni a yi ta, da kuma kiyaye lokutanta da sharuɗɗanta.
Ta biyu, bayar da dukiya sadaka ga mabuƙata domin tallafa musu da tsarkake dukiyar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babban musabbabin taɓewa a duniya da faɗawa cikin miyagun ayyuka shi ne rashin yin imani da ranar lahira.

2. Rashin imani da ranar lahira yakan jefa mutum cikin ruɗu da ɗimuwa a rayuwarsa, don ya kasa gane manufar zuwansa duniya.

3. Mummunan hali da waɗanda ba su yi imani da lahira ba suke tsintar kansu a cikinsa a nan duniya na kisa da ɗauri yayin da suka yi fito-na-fito da muminai, kamar yadda ya faru gare su a yaƙin Badar.

4. Azabar lahira ce mafi girman hasara, domin ba za ta yanke wa kafirai ba har abada saɓanin azabar duniya, ita mai ƙarewa ce.

Suratun Namli (4-5)

إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ زَيَّنَّا لَهُمۡ أَعۡمَٰلَهُمۡ فَهُمۡ يَعۡمَهُونَ ٤ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَهُمۡ سُوٓءُ ٱلۡعَذَابِ وَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ هُمُ ٱلۡأَخۡسَرُونَ ٥

4. Lalle waɗanda ba sa imani da ranar lahira Mun ƙawata musu ayyukansu, don haka suke ɗimuwa.

5. Waɗannan su ne waɗanda suke da mummunar azaba, kuma su ne suka fi hasara a lahira.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda ba su yi imani da ranar

lahira ba, da cewa shi ne ya ƙawata musu miyagun ayyukansu har suka riƙa ganin su kyawawa, sakamakon ƙaryata shi da suka yi da ƙaryata manzanninsa, don haka suka doge a kan aikata munanan ayyuka, suka ci gaba da zama cikin ɗimuwa da kasa gane gaskiya.
Ya bayyana cewa mutane masu irin waɗannan siffofi za su gamu da mummunar azaba a nan duniya ta hanyar karkashe su a wurin yaƙi, ko kama su a matsayin fursunonin yaƙi, a lahira kuma su ne suka fi kowa hasara, domin za su yi hasarar kawunansu da iyalansu, su kuma shiga wutar Jahannama su dawwama a cikinta har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba a ɗaukar karatun Alƙur'ani sai ta hanyar koyo daga wajen makarantan sa. Shi kansa Annabi (ﷺ) Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne ya koya masa karatunsa.

2. Idan har Alƙur'ani ya tabbata daga Allah Mai hikima Masani yake, to dole ne mu yarda da cewa dukkansa hikima ce, kuma ya ƙunshi maslahohin bayi ne domin ya zo ne daga wanda ya fi kowa sanin maslahar halittunsa.

3. Yana daga cikin imani da buwayar Allah, bawa ya dogara gare shi kada ya ji tsoron komai yayin da ya keɓanta da shi, domin makwarkwaɗar kowa da komai tana hannunsa, shi ne yake yin yadda ya so da bayinsa.

4. Tsoro wata ɗabi'a ce ta ɗan'adam, don haka ba abin kushewa ba ne don mutum ya ji tsoron wani abin tsoro, domin annabawa duk da girman darajarsu da babban matsayinsu da cikar dogaronsu da Allah, sukan ji tsoron abin ban tsoro.

5. Duk wanda ya zalunci kansa ta hanyar saɓa wa Ubangijinsa sannan ya tuba ya canja miyagun halayensa da kyawawan halaye, to ya sani Allah mai gafara ne, mai jin ƙai, don haka kada ya ɗebe ƙauna daga samun rahamar Allah da gafararsa.

6. Mafi yawan masu ƙaryata gaskiya suna jayayya da ita, a zukatansu sun san gaskiya ce, su kuma ƙarya suke kai, to amma zalunci da girman kai da son yaɗa ɓarna a bayan ƙasa shi ne yake hana su sallamawa da miƙa wuya ga gaskiyar.

7. Gargaɗi da jan hankali ga mushirikan Larabawa waɗanda suke jayayya da Manzon Allah (ﷺ), suke ƙaryata abin da ya zo musu da shi na hujjoji bayyanannu daga Allah, cewa su shiga hankalinsu kada irin azabar da ta sami Fir'auna da mutanensa su ma ta same su. Domin idan jayayya da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ƙaryata hujjojinsa ta jawo wa Fir'auna da mutanensa hallaka, to ina kuma ga masu jayayya da Annabi Muhammadu (ﷺ) wanda matsayinsa a wurin Allah ya fi na Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuma girman hujjojinsa sun fi nasa?!

8. Bayar da labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga bakin Annabi (ﷺ) babban dalili ne da ke nuna gaskiyar annabcinsa, domin wannan yana daga cikin gaibin da Manzon Allah (ﷺ) ba zai san shi ba sai ta hanyar wahayi.

Suratun Namli (6-14)

وَإِنَّكَ لَتُلَقَّى ٱلْقُرْءَانَ مِن لَّدُنْ حَكِيمٍ عَلِيمٍ ۝٦ إِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِأَهْلِهِۦٓ إِنِّىٓ ءَانَسْتُ نَارًا سَاٰتِيكُم مِّنْهَا بِخَبَرٍ أَوْ ءَاتِيكُم بِشِهَابٍ قَبَسٍ
لَّعَلَّكُمْ تَصْطَلُونَ ۝٧ فَلَمَّا جَآءَهَا نُودِىَ أَنۢ بُورِكَ مَن فِى ٱلنَّارِ وَمَنْ حَوْلَهَا وَسُبْحَٰنَ ٱللَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ۝٨ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّهُۥٓ أَنَا ٱللَّهُ ٱلْعَزِيزُ
ٱلْحَكِيمُ ۝٩ وَأَلْقِ عَصَاكَ ۚ فَلَمَّا رَءَاهَا تَهْتَزُّ كَأَنَّهَا جَآنٌّ وَلَّىٰ مُدْبِرًا وَلَمْ يُعَقِّبْ ۚ يَٰمُوسَىٰ لَا تَخَفْ إِنِّى لَا يَخَافُ لَدَىَّ ٱلْمُرْسَلُونَ ۝١٠ إِلَّا مَن ظَلَمَ
ثُمَّ بَدَّلَ حُسْنًۢا بَعْدَ سُوٓءٍ فَإِنِّى غَفُورٌ رَّحِيمٌ ۝١١ وَأَدْخِلْ يَدَكَ فِى جَيْبِكَ تَخْرُجْ بَيْضَآءَ مِنْ غَيْرِ سُوٓءٍ ۖ فِى تِسْعِ ءَايَٰتٍ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَقَوْمِهِۦٓ ۚ إِنَّهُمْ
كَانُوا۟ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ۝١٢ فَلَمَّا جَآءَتْهُمْ ءَايَٰتُنَا مُبْصِرَةً قَالُوا۟ هَٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ ۝١٣ وَجَحَدُوا۟ بِهَا وَٱسْتَيْقَنَتْهَآ أَنفُسُهُمْ ظُلْمًا وَعُلُوًّا ۚ فَٱنظُرْ كَيْفَ
كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلْمُفْسِدِينَ ۝١٤

6. Lalle kuma kai tabbas ana yi maka wahayin Alƙur'ani ne daga wajen (Allah) Mai hikima, Masani.

7. Ka tuna lokacin da Musa ya ce da iyalinsa: "Lalle ni na hango wata wuta, to (zan je) in zo muku da labari, ko kuma in zo muku da ɗosanen garwashi don ku ji ɗumi."

8. To lokacin da ya zo mata (wutar) sai aka kira shi cewa, an tsarkake wanda yake cikin wutar da waɗanda suke daura da ita (wato mala'iku), kuma tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

9. Ya Musa, lalle lamarin dai, Ni ne Allah Mabuwayi, Mai hikima.

10. Kuma ka jefar da sandarka. To lokacin da ya gan ta tana jujjuyawa kamar macijiya, sai ya juya da baya a guje bai dawo ba. (Allah ya ce): Ya Musa, kada ka ji tsoro, lalle Ni manzanni ba sa jin tsoro a wurina.

11. Sai dai wanda ya zalunci (kansa), sannan ya musanya kyakkyawa bayan mummuna, to lalle Ni Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

12. Kuma ka saka hannunka cikin wuyan rigarka, zai fito fari fat ba na cuta ba; (wannan aya ce) daga cikin ayoyi tara zuwa ga Fir'auna da mutanensa. Lalle su sun kasance mutane ne fasiƙai.

13. To lokacin da ayoyinmu waɗanda suke a sarari suka zo musu, sai suka ce: "Wannan sihiri ne mabayyani."

14. Suka kuma musanta su don zalunci da girman kai, alhali kuwa zukatansu sun sakankance da su. To sai ka duba ka ga yadda ƙarshen maɓarnata ya kasance.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara yin magana da Manzonsa inda ya tabbatar masa da cewa lalle wannan Alƙur'ani ne wanda aka saukar masa shi daga Allah mai hikima wajen gudanar da al'amuran bayinsa, kuma mai cikakken sani game da halayen bayinsa da abin da suke ciki, don haka duk hukuncinsa adalci ne, duk wani labarinsa kuma gaskiya ne.
Sai Allah ya umarci Manzonsa da ya gaya wa mutanensa labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da ya baro garin Madyana tare da iyalansa. Yana cikin tafiya tsakiyar saharar Sina'a sai ya ɓace hanya cikin dare mai duhu ga kuma tsananin sanyi, inda ya hango wata wuta tana ci daga nesa, kusa da wani dutsi da ake kiran sa Dutsen Ɗuri. Sai ya umarci iyalansa da su sami wuri su zauna, shi zai tafi wajen wannan wutar don ya zo musu da labarin hanyar da za su bi ta kai su Masar daga masu hura wutar, ko kuma ya zo musu da wani garwashin wuta domin su ji ɗumi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya isa wurin wannan wutar sai kawai ya ji ana kiran sa cewa, an yi albarka da tsarkakewa ga wanda yake cikin wannan wutar da waɗanda suke gefenta, watau mala'iku. Tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin halittu gaba ɗaya.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya tsaya a cikinmu ya ambata mana wasu kalmomi biyar ya ce: "Lalle Allah mai girma da buwaya ba ya barci, kuma ba ya dacewa a gare shi ya yi barci; yana ƙasa-ƙasa da mizanin adalci yana kuma yin sama da shi; ana kuma ɗaukaka masa ayyukan dare kafin na rana da ayyukan rana kafin na dare; shamakinsa haske ne – a ruwayar Abubakar ya ce wuta ce – da a ce zai yaye shi da hasken fuskarsa ya ƙone dukkan abin da ganinsa ya tuƙe gare shi na halittarsa." [Muslim #179].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a nan ne ya kira Annabi Musa da sunansa, ya tabbatar masa da cewa shi ne Allah Gagara-badau Mabuwayi wanda ya fi ƙarfin kowa, kuma mai hikima cikin dukkan lamuransa na halitta da ƙaddara da shari'a. Sai ya umarce shi da ya jefar da sandar da take hannunsa, nan take Annabi Musa ya jefar da ita, sai kuwa ta zama wata ƙatuwar macijiya tana jujjuyawa tana tafiya da sauri. Sai tsoro ya kama Annabi Musa ya juya a guje bai dawo ba, sai Allah ya umarce shi da ya dawo ya kuma daina jin wani tsoro, domin shi Manzonsa ne kuma a gabansa yake, manzanni kuwa a gaban Allah ba sa jin tsoron komai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi albishir ga duk wanda ya zalunci kansa ta hanyar aikata mummunan aiki sannan ya tuba ya nemi gafarar Allah, to Allah yana tabbatar masa da cewa shi mai gafara ne gare shi mai jin ƙan sa ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya shigar da hannunsa a cikin rigarsa, ya haɗa shi da kwiɓin jikinsa, to hannun zai fito fari yana haske kamar fitila ba kuma tare da wata cuta ba kamar albaras. Wannan yana daga cikin ayoyi guda tara masu tabbatar da gaskiyar manzancinsa, waɗanda suka haɗa da shekarun fari da tawayar kayan amfanin gona da ruwan Ɗufana da fari da ƙwarƙwata da kwaɗi da jini. Duk waɗannan mu'ujizoji ne ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa Fir'auna da mutanensa, saboda sun tabbata mutane ne fasiƙai waɗanda suka kauce wa ɗa'a ga Allah suka zaɓi hanyar kafirci.
Bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya je wa Fir'auna da jama'arsa da waɗannan hujjoji bayyanannu waɗanda suka gani da idanuwansa, sai kawai suka zarge shi da cewa ya zo musu da sihiri ne a fili. Allah ya tabbatar da cewa Fir'auna da mutanensa jayayya kawai suke yi da ayoyin Allah bayyanannu, suna nuna rashin yardarsu da su bayan kuma sun tabbatar da cewa daga Allah waɗannan ayoyin suke, saboda zaluncinsu da girman kansu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya duba ya ga yadda ƙarshen maɓarnata ya zama, watau yadda Allah ya hallakar da su baki ɗaya kamar ma ba a taɓa yin su a doron ƙasa ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nutsar da Fir'auna da rundunarsa cikin ruwa suka hallaka, ya kuma tserar da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Banu Isra'ila daga mummunan makircinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman falalar ilimi, duba da yadda Annabi Dawudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ɗansa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka nuna cewa ilimi shi ne ginshiƙin duk wata falala da Allah ya yi musu. Ba su ma ambaci sauran dangogin ni'ima na duniya ba, kamar mulki da dukiya da Allah ya ba su.

2. Annabawa ba a gadar dukiyarsu da abin da suka mallaka na duniya. Ana gadar ilimin annabawa ne. Annabi (ﷺ) yana cewa: “Mu jama’ar annabawa ba a cin gadonmu, abin da muka bari sadaka ne.” [Dubi An-Nasa’i, *As-Sunan Al-Kubra* #6275].

Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba dukiya ce ya gada a wajen mahaifinsa Annabi Dawudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba, domin da a ce maganar gadon dukiya ake yi, to da ba ta kɓanta da Annabi Sulaimanu ban da sauran ‘ya’yan Annabi Dawud ba.

3. Bawa ya riƙa ambaton ni’imomin da Allah ya yi masa yana daga cikin bayyana godiya gare shi.

4. Gabanin Annabi Dawud da Annabi Sulaimanu babu wani mutum da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fahimtar da shi maganar tsuntsaye.

Suratun Namli (15-16)

وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا دَاوُۥدَ وَسُلَيۡمَٰنَ عِلۡمٗاۖ وَقَالَا ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي فَضَّلَنَا عَلَىٰ كَثِيرٖ مِّنۡ عِبَادِهِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٥ وَوَرِثَ سُلَيۡمَٰنُ دَاوُۥدَۖ وَقَالَ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ عُلِّمۡنَا مَنطِقَ ٱلطَّيۡرِ وَأُوتِينَا مِن كُلِّ شَيۡءٍۖ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ ٱلۡفَضۡلُ ٱلۡمُبِينُ ١٦

15. Haƙiƙa kuma Mun bai wa Dawuda da Sulaimana ilimi; suka kuma ce: “Godiya ta tabbata ga Allah wanda Ya fifita mu a kan masu yawa daga bayinsa muminai.”

16. Sulaimanu kuma ya gaji Dawuda; ya kuma ce: “Ya ku waɗannan mutane, (wato Yahudawa), an sanar da mu zancen tsuntsaye, kuma an ba mu daga kowane abu (na tafiyar da mulki); lalle wannan tabbas ita ce bayyananniyar falala.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar da wani ɓangare na labarin Annabi Dawud da Annabi Sulaiman , biyu daga cikin annabawan Banu Isra’ila. Allah ya tabbatar da cewa ya ba su wani ilimi mai girma, daga ciki har da ilimin fahimtar maganar tsuntsaye, kamar yadda ya koyar da Annabi Dawud sana’ar ƙira, sai suka bayyana godiyarsu ga Allah wanda ya fifita su a kan muminai da dama, ya kuma ba su matsayi na annabci, ya hore wa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sarrafa aljannu da shaiɗanu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gaji mahaifinsa Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), gadon ilimi da annabta da Allah ya ba shi, kamar yadda kuma ya gaji mulkinsa wanda Allah ya faɗaɗa masa shi, watau ya ninka masa ƙarfinsa, saboda haka ne Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana ni’imomin da Allah ya yi musu ga mutane da cewa Allah ya hore musu hanyoyin fahimtar maganar tsuntsaye, ya kuma hore musu dukkan abin da ake bai wa annabawa da sarakuna, sai kuma ya tabbatar musu da cewa wannan ita ce falala ta zahiri da Allah ya yi musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tururuwa ta yi nasiha ga ‘yan’uwanta taron tururuwa, Allah kuma ya isar da saƙonta ga dukkan tururuwar da suka cika wannan kwarin. Wannan wani babban abin mamaki ne da ya taɓa faruwa. Yana yiwuwa Allah ya hore mata murya ce wadda ta kai ga duk wata tururuwa da ke wannan wuri; yana yiwuwa kuma ta yi maganar ne da na kusa da ita sai maganar ta bazu a tsakaninsu.

2. Ishara a kan tausayin ƙwari a junansu. Da yawa wasu ƙwarin kamar wannan tururuwar sun fi tausayin junansu a kan yawancin ‘yan’adam, duba da yadda a yau ɗan’adam yake kashe jinsinsa ba bisa haƙƙi ba, suna jefa junansu cikin masifu da tashe-tashen hankula da hallaka juna.

3. Annabi Sulaimanu bai san gaibu ba. Hakanan aljannun da ke tare da shi a cikin rundunoninsa ba su san gaibu ba, domin ba su san da waɗannan taron tururuwar ba, shi ya sa aka nuna yiwuwar su tattake su ba tare da sun sani ba.

4. Bayanin adalcin Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) hatta ga ƙwari, domin da ya san da su to ba zai tattake su ba, zai yi ƙoƙarin kauce musu.
5. Murmushi shi ne yawancin dariyar annabawa da nutsattsun mutane.

6. Gode wa ni’imomin Allah al’ada ce ta annabawa da mutane na gari.

7. Nema wa mutanen kirki uzuri alhalin ba su san me yake faruwa ba, kamar yadda tururuwa ta kyautata zato ga Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da rundunarsa.

Suratun Namli (17-19)
وَحُشِرَ لِسُلَيۡمَٰنَ جُنُودُهُۥ مِنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِ وَٱلطَّيۡرِ فَهُمۡ يُوزَعُونَ ١٧ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَتَوۡاْ عَلَىٰ وَادِ ٱلنَّمۡلِ قَالَتۡ نَمۡلَةٞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّمۡلُ ٱدۡخُلُواْ مَسَٰكِنَكُمۡ لَا يَحۡطِمَنَّكُمۡ سُلَيۡمَٰنُ وَجُنُودُهُۥ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ١٨ فَتَبَسَّمَ ضَاحِكٗا مِّن قَوۡلِهَا وَقَالَ رَبِّ أَوۡزِعۡنِيٓ أَنۡ أَشۡكُرَ نِعۡمَتَكَ ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتَ عَلَيَّ وَعَلَىٰ وَٰلِدَيَّ وَأَنۡ أَعۡمَلَ صَٰلِحٗا تَرۡضَىٰهُ وَأَدۡخِلۡنِي بِرَحۡمَتِكَ فِي عِبَادِكَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١٩

17. Aka kuma tattara wa Sulaimanu rundunoninsa na aljannu da mutane da kuma tsuntsaye, sai aka riƙa turo su sahu-sahu.

18. Har dai zuwa lokacin da suka iso kwarin tururuwa, sai wata tururuwa ta ce: “Ya ku waɗannan taron tururuwa, ku shige gidajenku kada Sulaimanu da rundunoninsa su tattake ku alhali kuwa ba da saninsu ba.”

19. Sai ya yi murmushi yana mai dariya saboda maganarta, ya kuma ce: “Ubangijina Ka kimsa min yadda zan gode wa ni’imar da Ka yi min ni da mahaifana, da kuma yadda zan yi aiki na gari wanda za Ka yarda da shi, kuma Ka shigar da ni don rahamarka cikin bayinka na gari.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kaɗan daga cikin ni’imomin da ya yi wa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da cewa an tattaro masa da rundunoninsa daga aljannu da mutane da tsuntsaye, sai aka riƙa turo su cikin wani tsari mai ban sha’awa. Suka yi ta tafiya cikin tsari sahu-sahu har sai da suka iso kwarin tururuwa, wani wuri ne a ƙasar Sham, sai wata tururuwa ta kira sauran ‘yan’uwanta taron tururuwa ta ba su umarni da su koma cikin gidajensu don kada Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da rundunar sojojinsa su tattake su su mutu ba tare da sun sani ba.
Yayin da Annabi Sulaimanu ya ji maganar wannan tururuwa sai ya yi murmushi yana dariya, saboda farin cikin jin wannan magana tata, sannan ya roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kimsa masa gode wa ni’imar da ya yi masa da ya ba shi ikon fahimtar maganganun tsuntsaye da ƙwari da kuma ni’imar da ya yi wa iyayensa. Ya kuma roƙe shi ya ba shi ikon yin aiki na ƙwarai wanda zai yarda da shi, watau wanda ya dace da umarnin Allah tare da yin ikhlasi a cikinsa, kuma ya roƙi shi ya sanya shi cikin jimillar bayinsa na gari da tsantsar rahamarsa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wata tururuwa ta ciji wani daga cikin annabawa sai ya ba da umarni a ƙone alƙaryar tururuwar gaba ɗaya. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa wahayi cewa: “Don kawai wata tururuwa ta cije ka sai ka hallakar da al’umma guda wadda take yi wa Allah tasbihi?” [Bukhari #3019 da Muslim #224].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abu ne mai matuƙar muhimmanci shugaba ya riƙa bibiyar talakawansa yana sanin halin da jama’arsa suke ciki, don sanin abin da suke buƙata daga gare shi.

2. Gudanar da shugabancin al’umma ta hanyar hukunta duk wanda ya kamata a hukunta shi, da karɓar hanzarin wanda yake da hanzari ƙwaƙƙwara.

3. Za a iya samun wani abu na ilimi a wurin ƙanana na ƙasa wanda ba lalle a same shi ba a wurin manya.

4. Shugabancin mace al’ada ce daɗaɗɗiya a cikin al’ummun da ba su san shari’ar Allah da shiriyar annabawa ba.

5. Shaiɗan yakan ƙawata mummunan aiki ga wasu mutane su riƙa ganin sa abu ne mai kyau suna sha’awar sa.

6. Tsuntsu Alhudahuda ya nuna ƙyamarsa da damuwarsa a kan bautar wani abu ba Allah ba. Wannan shi yake nuna cewa kaɗaita Allah da bauta, watau *Tauhidi*, wani muhimmin al’amari ne da Allah ya kimsa a zukatan halittunsa baki ɗaya har da tsuntsaye.

7. Babu wani nassi sahihi da ya bayyana sunan wannan Sarauniyar, amma malaman tafsiri da dama da na tarihi sun ce sunanta Bilƙisu ‘yar Shurahbilu.

8. Alhudahuda ya girmama sha’anin mulkin Sarauniyar Saba’u domin ya fahimci Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba ya da masaniya a kan wannan mata da masarautarta da kuma yadda ya fahimci ƙoƙarin da yake yi na isar da saƙon Tauhidi da yaƙar shirka a bayan ƙasa. Wannan labari da ya zo wa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da shi ko shi kaɗai ya isa ya zama ƙwaƙƙwaran uzuri da zai sa ya yi masa afuwa na rashin ganin sa da ya yi.

Suratun Namli (20-26)

وَتَفَقَّدَ ٱلطَّيۡرَ فَقَالَ مَا لِيَ لَآ أَرَى ٱلۡهُدۡهُدَ أَمۡ كَانَ مِنَ ٱلۡغَآئِبِينَ ٢٠ لَأُعَذِّبَنَّهُۥ عَذَابٗا شَدِيدًا أَوۡ لَأَاْذۡبَحَنَّهُۥٓ أَوۡ لَيَأۡتِيَنِّي بِسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٖ ٢١ فَمَكَثَ غَيۡرَ بَعِيدٖ فَقَالَ أَحَطتُ بِمَا لَمۡ تُحِطۡ بِهِۦ وَجِئۡتُكَ مِن سَبَإِۭ بِنَبَإٖ يَقِينٍ ٢٢ إِنِّي وَجَدتُّ ٱمۡرَأَةٗ تَمۡلِكُهُمۡ وَأُوتِيَتۡ مِن كُلِّ شَيۡءٖ وَلَهَا عَرۡشٌ عَظِيمٞ ٢٣ وَجَدتُّهَا وَقَوۡمَهَا يَسۡجُدُونَ لِلشَّمۡسِ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَعۡمَٰلَهُمۡ فَصَدَّهُمۡ عَنِ ٱلسَّبِيلِ فَهُمۡ لَا يَهۡتَدُونَ ٢٤ أَلَّا يَسۡجُدُواْ لِلَّهِ ٱلَّذِي يُخۡرِجُ ٱلۡخَبۡءَ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَيَعۡلَمُ مَا تُخۡفُونَ وَمَا تُعۡلِنُونَ ٢٥ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ رَبُّ ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡعَظِيمِ ٢٦

20. Kuma ya bincika tsuntsaye, sai ya ce: “Me ya sa ba na ganin Alhudahuda, ko kuwa yana cikin waɗanda ba sa nan ne?

21. “Na rantse zan yi masa azaba mai tsanani, ko kuma tabbas zan yanka shi, ko kuma lalle ya zo min da hujja bayyananna.”

22. Sai ko ba da daɗewa ba ya dawo, sannan (bayan an tambaye shi) ya ce: “Ni fa na gano abin da ba ka sani ba, na kuma zo maka da tabbataccen labari daga birnin Saba’u.

23. “(Shi ne) lalle na sami wata mace tana mulkar su, an kuma ba ta daga kowane abu (na mulki), tana kuma da gadon sarauta mai girma.

24. “Na same ta ita da mutanenta suna sujjada ga rana ba Allah ba. Shaiɗan kuma ya ƙawata musu ayyukansu, sai ya kange su daga bin hanya ta gaskiya, don haka su ba sa kan shiriya.

25. “Don kada su yi sujjada ga Allah wanda Yake fito da abin da yake ɓoye a cikin sammai da ƙasa, kuma Yake sane da abin da kuke ɓoyewa da abin da kuke bayyanawa.

26. “(Shi ne) Allah Wanda babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, Ubangijin Al’arshi mai girma.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wata rana Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana bibiyar rundunoninsa na aljannu da mutane da tsuntsaye, lokacin da ya zo kan tsuntsaye sai bai ga Alhudahuda a cikinsu ba. Sai ya yi tambaya cewa, me ya sa bai ga Alhudahuda ba? Watau shi ne bai gan shi ba yana cikin ribibi ko kuma dai ba ya wurin ne? Sai aka sanar da shi cewa ba ya nan. Sai Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi barazanar cewa lalle idan ya dawo sai ya yi masa azaba mai tsanani, ko ya yanka shi sakamakon rashin ganin sa da ya yi, ko kuma ya zo masa da wata bayyananniyar hujja karɓaɓɓiya wadda za ta nuna uzurinsa a fili.
Ba a jima ba kuma sai ga Alhudahuda ya dawo, ya bayyana wa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) uzurinsa na rashin halarta a kan kari, da cewa ya gano masa wani abu da shi bai san da shi ba, domin ya zo masa da wani sahihin labari wanda babu kokwanto a cikinsa daga birnin Saba’u na ƙasar Yaman. Watau ya samu mutanen wannan birnin wata mata ce take mulkinsu, kuma an ba ta duk wani abu da mulkinta yake buƙata na ƙarfin mayaƙa da tattalin arziki, sannan kuma tana da wani gadon sarauta mai girman gaske wanda takan hau shi don gudanar da sha’anin mulkinta.
Alhudahuda ya ci gaba da bayyana wa Annabi Sulaimanu abin da ya gano a birnin Saba’u, da cewa ya sami wannan mata mai mulki da mutanenta suna bautar rana ne ba Allah ba, kuma Shaiɗan ne ya ƙawata musu ayyukan shirka da saɓon Allah da suke yi, ya kuma hana su bin hanyar gaskiya, don haka suka kasa shiryuwa su bauta wa Allah shi kaɗai wanda yake fito musu da ruwan da yake ɓoye a sama, da tsirran da suke cikin ƙasa, kuma yake sane da ayyukansu da suke ɓoyewa da waɗanda suke bayyanawa. Shi ne Allah wanda babu abin bauta da gaskiya sai shi Ubangijin Al’arshi mai girma.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bincike don tabbatar da gaskiyar labari kafin ɗaukar wani mataki a kansa.

2. Yana da kyau masu mulki su riƙa binciken sanin abin da maƙiyansu suke ciki.

3. Halaccin mai rubuta wasiƙa ya fara da faɗar sunansa.

4. Yana da kyau buɗe wasiƙa da Bismilla ko da kuwa za a aika ta zuwa ga abokan gaba.

5. Abu ne mai matuƙar muhimmanci masu gaskiya su riƙa nuna izzarsu a gaban mabiya tafarkin ƙarya.

6. Ayoyin sun nuna abubuwa kamar haka:

• Saurin Alhudahuda wajen isar da wannan wasiƙar zuwa ga Sarauniya da mutanenta.
• Alhudahuda yana da ƙarfin fahimta, don haka ya fahimci duk maganar da suke yi.
• Nan take bayan wasiƙar ta sami sarauniya ta umarci masu yi mata fassara suka fassara mata ita.

7. Wasiƙar ta ƙunshi muhimman abubuwa na addini da rayuwa, su ne:
• Tabbatar da samuwar Allah da Kaɗaitakarsa da Kudurarsa da kasancewarsa mai rahama mai jin ƙai.
• Hana su bin son zukatansu da wajabcin su bi gaskiya.
• Umartar su da su je masa suna masu miƙa wuya.

Suratun Namli (27-31)

۞قَالَ سَنَنظُرُ أَصَدَقْتَ أَمْ كُنتَ مِنَ ٱلْكَٰذِبِينَ ﴿٢٧﴾ ٱذْهَب بِّكِتَٰبِى هَٰذَا فَأَلْقِهْ إِلَيْهِمْ ثُمَّ تَوَلَّ عَنْهُمْ فَٱنظُرْ مَاذَا يَرْجِعُونَ ﴿٢٨﴾ قَالَتْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْمَلَؤُا۟ إِنِّىٓ أُلْقِىَ إِلَىَّ كِتَٰبٌ كَرِيمٌ ﴿٢٩﴾ إِنَّهُۥ مِن سُلَيْمَٰنَ وَإِنَّهُۥ بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ﴿٣٠﴾ أَلَّا تَعْلُوا۟ عَلَىَّ وَأْتُونِى مُسْلِمِينَ ﴿٣١﴾

27. Sai (Sulaimana) ya ce: “To za mu duba ko ka yi gaskiya ko kuwa ka zama cikin maƙaryata.

28. “Ka tafi da wannan wasiƙar tawa sai ka jefa musu ita sannan ka ja da baya kaɗan, sai ka ga da me za su mayar da martani?”

29. Sai ta ce: “Ya ku manyan fada, lalle an jefo min wata wasiƙa mai daraja.

30. “(Mai cewa): Lalle wannan (wasiƙar) daga Sulaimana ne kuma lalle ina farawa da *Bismillahi Arrahamani Arrahim*.

31. “Kada ku yi min girman kai, ku zo min kuna masu miƙa wuya!”

A waɗannan ayoyi, bayan Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ji duk bayanan Alhudahuda, sai ya bayyana masa cewa za su duba su yi bincike don tabbatar da gaskiyar labarinsa ko ƙaryarsa, watau kafin su san irin matakin da za su ɗauka a kai.
Daga nan sai Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fara ɗaukar matakin bincike, ya rubuta taƙaitacciyar wasiƙa ya ba Alhudahuda don ya isar da ita ga Sarauniyar Saba’u, ya umarce shi da ya je garin ya jefa musu wannan wasiƙar, sai ya ɗan ja da baya kaɗan ya tsaya inda zai ji abin da Sarauniya da fadawanta za su tattauna a kansa da kuma irin martanin da za su dawo da shi.
Bayan Alhudahuda ya aikata abin da aka umarce shi da shi, wasiƙa ta je hannun Sarauniyar Saba’u, ta kuma karanta ta ga abin da yake ciki, sai ta tara manyan gari a fadarta ta faɗa musu cewa an fa jefo mata wasiƙa mai girma. Abin da ta ƙunsa kuwa shi ne, “Wannan wasiƙa daga Sulaimanu take” kuma an buɗe ta da Bismilla, watau “Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai”. Sannan wasiƙar ta ce: “Lalle kada ku yi min girman kai, ku zo min kuna masu miƙa wuya”. Watau dai yana sanar da su cewa kada su bijire masa, su zo suna masu miƙa wuya ga abin da yake kiran su a kai na kaɗaita Allah da barin shirkar da suke kai ta bautar rana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin zurfin hankalin Sarauniyar Saba’u da ƙwarewarta wajen gudanar da sha’anin mulki, domin ta fahimci muhimmancin neman shawara cikin manyan al’amuran mulki.

2. Fadawan Sarauniya sun nuna mata cewa su a shirye suke su fuskanci yaƙi da Annabi Sulaiman a kan su amsa kiransa na su miƙa wuya gare shi. To amma duk da haka sai suka nuna mata cewa ita ce mai magana ta ƙarshe, kuma duk abin da ta yanke ya yanku za su kuma yi mata ɗa'a a kai. Wannan ya nuna ƙarfin mulkinta da biyayyar al'ummarta a gare ta.

3. Tasirin kyauta wajen sassauta ra'ayin mutum ko sauko da shi daga kan abin da ya yi niyya.

4. Kafa hujja da dalilai na tarihi. Sarauniya ta fifita warware matsalarsu da masarautar Annabi Sulaimanu ta hanyar lalama ba ta hanyar yaƙi ba. Domin a iya saninta da tarihin yaƙe-yaƙen sarakuna, duk wani sarki da ya yi yaƙi da wata ƙasa ya kuma sami nasara a kanta, to farkon abin da zai yi bayan ya ƙwaci mulki shi ne ya canja tsarin mulkin wannan ƙasa ta yadda zai dace da maslaharsa da buƙatarsa, sannan ya tsige duk tsofaffin masu riƙe da muƙamai ya kawo nasa sababbi, don tsoron kada su zamo masa matsala a gaba. Sannan ba ya ga haka, idan da ƙarfi ya karɓi wannan ƙasa, to yana da wuya yaƙi ya ƙare ba tare da an yi gagarumar ɓarna ta salwantar rayuka da dukiyoyi ba da kamen bayi da fursunonin yaƙi da jefa su cikin wulaƙanci da ƙaskanci. Wannan shi ne abin da Sarauniya ta hararo ta kuma kafa hujja da abin da ta sani na tarihin sarakuna.

5. Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ƙi karɓar kyautar Sarauniya ne ba domin ita kafira ba ce, saboda karɓar kyautar kafiri ba laifi ba ne, Annabi (ﷺ) ya karɓi kyautar Al-Muƙaukis Shugaban Kibɗawan Masar tare da kasancewarsa kafiri. Sai dai Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ƙi karɓa ne saboda ya fahimci manufar kyautar, watau shi ne ƙokarin hana shi zartar da abin da Allah ya umarce shi da shi na isar da saƙon Tauhidi ga al'ummun zamaninsa.

Suratun Namli (32-37)

قَالَتْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْمَلَؤُا۟ أَفْتُونِى فِىٓ أَمْرِى مَا كُنتُ قَاطِعَةً أَمْرًا حَتَّىٰ تَشْهَدُونِ ﴿٣٢﴾ قَالُوا۟ نَحْنُ أُو۟لُوا۟ قُوَّةٍ وَأُو۟لُوا۟ بَأْسٍ شَدِيدٍ وَٱلْأَمْرُ إِلَيْكِ فَٱنظُرِى مَاذَا تَأْمُرِينَ ﴿٣٣﴾ قَالَتْ إِنَّ ٱلْمُلُوكَ إِذَا دَخَلُوا۟ قَرْيَةً أَفْسَدُوهَا وَجَعَلُوٓا۟ أَعِزَّةَ أَهْلِهَآ أَذِلَّةً ۖ وَكَذَٰلِكَ يَفْعَلُونَ ﴿٣٤﴾ وَإِنِّى مُرْسِلَةٌ إِلَيْهِم بِهَدِيَّةٍ فَنَاظِرَةٌۢ بِمَ يَرْجِعُ ٱلْمُرْسَلُونَ ﴿٣٥﴾ فَلَمَّا جَآءَ سُلَيْمَٰنَ قَالَ أَتُمِدُّونَنِ بِمَالٍ فَمَآ ءَاتَىٰنِۦَ ٱللَّهُ خَيْرٌ مِّمَّآ ءَاتَىٰكُم ۖ بَلْ أَنتُم بِهَدِيَّتِكُمْ تَفْرَحُونَ ﴿٣٦﴾ ٱرْجِعْ إِلَيْهِمْ فَلَنَأْتِيَنَّهُم بِجُنُودٍ لَّا قِبَلَ لَهُم بِهَا وَلَنُخْرِجَنَّهُم مِّنْهَآ أَذِلَّةً وَهُمْ صَٰغِرُونَ ﴿٣٧﴾

32. (Sai Sarauniyar) ta ce: "Ya ku manyan fada, ku ba ni shawara game da al'amarina, (domin) ni ba zan yanke (shawarar) wani al'amari ba sai kuna nan."

33. Sai suka ce: "Mu dai ƙarfafa ne kuma mayaƙa sosai, al'amarin kuwa yana hannunki, sai ki duba abin da za ki yi umarni."

34. Sai ta ce: "Lalle sarakuna idan suka shigo wata alƙarya sai su yi kaca-kaca da ita, kuma su mayar da manyanta ƙaskantattu; kuma haka suke aikatawa.

35. "Ni kam lalle zan aika musu ne da wata kyauta sannan in saurari abin da manzanni za su dawo da shi."

36. To lokacin da (manzo) ya zo wa Sulaimanu sai ya ce: "Yanzu kwa ƙare ni da wata dukiya, alhali abin da Allah Ya ba ni ya fi wanda Ya ba ku? A'a, ku ne kuke farin ciki da kyautarku.

37. "Koma musu (da kyautarsu) sannan (ka gaya musu) lalle za mu zo musu da runduna wadda ba za su iya tunkarar ta ba, kuma lalle za mu fitar da su daga cikinta (alƙaryar) a wulaƙance suna ƙaskantattu!"

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Sarauniyar birnin Saba'u ta tara manyan gari ta nemi shawararsu, ta kuma tabbatar musu da cewa ba za ta yanke komai ba a kan wannan al'amari har sai ta saurari ra'ayinsu.
Sai suka mayar mata da jawabi da cewa, su mutane ne ƙarfafa kuma jaruman mayaƙa, saboda haka ko da ta bijire wa Annabi Sulaimanu ta ƙi yarda da shi, to su a shirye suke su fafata yaƙi a kan haka, amma dai sai suka mayar da magana gare ta domin sun yarda da cewa ita mace ce mai zurfin hankali, don haka ba za ta yanke abin da bai dace ba, kuma a shirye suke su zartar da duk abin da ta umarce su.
Sai Sarauniya ta bayyana musu illar yaƙi da sarakuna masu ƙarfi da cewa, idan har suka yi nasarar kama wata alƙarya, to fa sai sun yi babbar ɓarna a cikinta, sun yi kashe-kashe sun wawashe dukiyar al'umma, sun kama manyan garin sun mayar da su wulaƙantattu sun bautar da su. Ta kuma tabbatar musu cewa koyaushe haka halin sarakunan yake.
A ƙarshe dai ta zartar da nata tunani da cewa, za ta fito musu ta hanyar lalama, ta aika masa da kyauta ta alfarma, don ta ga ko wannan zai canza masa ra'ayinsa ko kuma a'a. Sai ta aika wasu manyan fadawanta da kyauta zuwa ga Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Yayin da suka isa gare shi suka ƙaddamar masa da kyautar Sarauniya sai ya ƙi karɓar kyautarsu, ya kuma mayar musu da martani mai zafi da cewa, suna zato za su ƙare shi ne da wata dukiya don su canza masa tunaninsa ya fasa aikata abin da ya yi niyya? Don haka ya tabbatar musu da cewa abin da Allah ya ba shi ya zarce abin da suke taƙama da shi, domin shi Allah ya ba shi ƙasaitaccen mulkin da bai taɓa ba wa wani mahaluƙi irinsa ba, bugu da ƙari kuma ga shi Annabin Allah. Sai ya soke su da cewa su ne wannan kyautar za ta raɗa su da ƙasa har su yi ta farin ciki da ita, saboda son duniya da ke zukatansu da kuma ƙarancin abin da suka mallaka, idan an kwatanta shi da abin da shi ya mallaka.
Daga nan ne fa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya umarci wannan manzon na Sarauniya da 'yan rakiyarsa su koma su mayar mata da kyautarta sannan su isar mata da saƙonsa na cewa, tabbas ba makawa zai zo musu da rundunarsa da ba za su iya tunkarar ta ba, kuma lalle sai ya fitar da su daga garin Saba'u cikin wulaƙanci da ƙasƙanci matuƙar ba su sallama kansu gare shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya buƙaci a ɗauko masa gadon Sarauniya kafin su iso wajensa su miƙa wuya. Zahirin aya yana nuna cewa a lokacin Annabi Sulaimanu yana ƙasar Sham ne, tsakaninsa da ƙasar Saba'u kuwa tafiyar wata huɗu ce zuwa da dawowa.

2. Babu wani nassi da ya bayyana hikimar da ta sa Annabi Sulaimanu ya buƙaci a ɗauko masa gadon sarautar Sarauniya. Amma wasu malamai sun ce ya yi haka ne domin ya nuna mata ƙarfin mulkinsa. Wasu kuma suka ce, domin akwai tsammanin ta fito da shi zuwa ga Annabi Sulaimanu domin gudun kada a hana ta abin zama na masu sarauta, a zaunar da ita a mazauni na ƙasƙanci, sai ta yi tunanin ta ɗauko gadonta ta taho da shi, shi kuma Annabi Sulaimanu ya yi tunanin a kawo masa gadonta tun kafin isowarta.

3. A cikin aljannu wasu sun fi wasu ƙarfi kamar yadda mutane suke.

4. Amana wata siffa ce ta yabo har a wurin aljannu.

5. Karamar waliyyai gaskiya ce, tana kuma kasancewa ne ga mutumin da yake bin shari'ar Allah sau da ƙafa.

6. Ni'imomin Allah ga bawa jarrabawa ce ta Ubangiji don ya ga bawan nan zai gode masa ko zai butulce masa.

7. Tsananin tawali'un Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), bai nuna alfahari da ƙarfin mulkinsa ba kamar yadda jahilan sarakuna suke yi; sai ya nuna cewa wannan wata jarrabawa ce Allah ya yi masa, don haka ya ji tsoron kada ya zamanto ya kasa bayar da haƙƙinta na godiya da ya hau kansa.

Suratun Namli (38-40)

قَالَ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمَلَؤُاْ أَيُّكُمۡ يَأۡتِينِي بِعَرۡشِهَا قَبۡلَ أَن يَأۡتُونِي مُسۡلِمِينَ ٣٨ قَالَ عِفۡرِيتٞ مِّنَ ٱلۡجِنِّ أَنَا۠ ءَاتِيكَ بِهِۦ قَبۡلَ أَن تَقُومَ مِن مَّقَامِكَۖ وَإِنِّي عَلَيۡهِ لَقَوِيٌّ أَمِينٞ ٣٩ قَالَ ٱلَّذِي عِندَهُۥ عِلۡمٞ مِّنَ ٱلۡكِتَٰبِ أَنَا۠ ءَاتِيكَ بِهِۦ قَبۡلَ أَن يَرۡتَدَّ إِلَيۡكَ طَرۡفُكَۚ فَلَمَّا رَءَاهُ مُسۡتَقِرًّا عِندَهُۥ قَالَ هَٰذَا مِن فَضۡلِ رَبِّي لِيَبۡلُوَنِيٓ ءَأَشۡكُرُ أَمۡ أَكۡفُرُۖ وَمَن شَكَرَ فَإِنَّمَا يَشۡكُرُ لِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ رَبِّي غَنِيٌّ كَرِيمٞ ٤٠

38. Sai (Sulaimanu) ya ce: "Ya ku manyan fada, wane ne daga cikinku zai zo min da gadon mulkinta tun kafin su zo min suna masu miƙa wuya?"

39. Sai wani ifritu daga cikin aljannu ya ce: "Ni zan zo maka da shi kafin ka tashi daga majalisarka; lalle ni kuma mai ƙarfi ne amintacce game da (kawo) shi."

40. Sai wani (mutum) wanda yake da ilimin Littafi (na Attaura) ya ce: "Ni zan kawo maka shi kafin ka ƙifta idonka!" To lokacin da (Sulaimanu) ya gan shi ga shi nan a gabansa sai ya ce: "Wannan yana daga falalar Ubangijina don Ya jarraba ni (Ya gani) shin zan gode ne ko zan butulce; to duk wanda ya gode kansa ya yi wa; wanda kuwa ya butulce, to lalle Ubangijina Mawadaci ne, Mai karamci."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan manzannin Sarauniya sun koma domin isar da saƙon Annabi Sulaimanu zuwa gare ta sai ya tabbatar wa fadawansa cewa Sarauniya da mutanenta za su miƙa wuya gare shi, amma duk da haka sai ya tambayi fadawan da suke gabansa na mutane da aljannu cewa wane ne a cikinsu zai iya kawo masa gadon sarautarta tun kafin su zo su sallama kansu? Da jin wannan tambaya sai wani ƙaƙƙarfan aljani ya bayyana cewa shi zai iya kawo wa Annabi Sulaimanu wannan gadon kafin ya tashi daga majalisarsa. Ya kuma tabbatar masa da cewa shi ƙaƙƙarfa ne don haka ɗaukar wannan gado ba zai gagare shi ba, sannan kuma shi mai amana ne, ba zai taɓa komai daga jikin wannan gado ba.
Sai kuma wani salihin malami mai ilimin littafi da ke zaune a gaban Annabi Sulaimanu ya bayyana masa cewa shi zai iya kawo masa gadon kafin ma ya ƙifta idonsa. Faɗar wannan ke da wuya sai kawai Annabi Sulaimanu ya ga gado gingirin a gabansa. Sai ya ce tabbas wannan lamari ba komai ba ne sai falalar Ubangijinsa a gare shi, kuma ya yi masa haka ne don ya jarrabe shi ya ga shin zai gode wa Allah kan ɗimbin ni'imomin da ya yi masa ko zai butulce? Sannan ya bayyana cewa duk wanda ya gode wa Allah kansa ya yi wa, domin shi ne zai ga amfanin godiyar. Hakanan duk wanda ya butulce to don kansa, domin shi Allah mawadaci ne ba shi da buƙatar komai a wurin kowa, kuma mai karamci ne don haka ne ma yake ƙara wa bayi masu yi masa godiya a kullum.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kaifin basirar Sarauniya kamar yadda za a iya fahimtar haka daga amsar da ta bayar yayin da aka tambaye ta game da gadonta na sarauta aka ce mata: "Shin kamar haka gadonki yake?" Sai ba ta ce shi ne ba, kuma ba ta ce a'a, ba shi ne ba, sai kawai ta bayar da amsa mai harshen damo wadda za ta iya ƙunsar dukkan ma'anonin biyu.

2. Ni'imar shiriyar Musulunci da kuma ilimin sanin Allah tana gaba da kowace ni'ima da mutum zai samu a duniya.

3. Wanda ya riga samun ilimi to yana da falala da fifiko a kan wanda ya samu daga baya ko da kuwa ya zo ya zarce shi a wannan ilimin.

4. Rungumar miyagun aƙidu da yarda da su yana toshe basira ya hana ta gane gaskiya.

5. Babban abin izina daga labarin wannan Sarauniya shi ne yadda girman mulkinta da matsayinta da kaifin hankali da Allah ya ba ta duk ba su hana ta tsayawa ta yi duba na natsuwa game da dalilai masu tabbatar da aƙidar kaɗaita Allah ba da ɓacin hanyar shirka. Wannan shi ya sanya ta yi watsi da addininta na bautar rana ta rungumi addinin gaskiya wanda Annabi Sulaimanu ya kirawo ta zuwa gare shi. Wannan labari ya ƙara tabbatar da wautar mushirikan Larabawa waɗanda suka kafe a kan bin hanyar shirka da suka gada iyaye da kakanni, suka kasa natsuwa su dubi manyan dalilan da Annabi (ﷺ) ya zo musu da su masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah da manzancin Annabi (ﷺ).

6. An samu labarai da hikayoyi da dama a wannan ƙissa waɗanda ba su da wani ingantaccen tushe ko madogara. Don haka dole ne a taƙaita a kan abin da Alƙur'ani ya zo da shi domin shi ne gaskiyar da babu tababa a cikinta.

Suratun Namli (41-44)

قَالَ نَكِّرُواْ لَهَا عَرۡشَهَا نَنظُرۡ أَتَهۡتَدِيٓ أَمۡ تَكُونُ مِنَ ٱلَّذِينَ لَا يَهۡتَدُونَ ﴿٤١﴾ فَلَمَّا جَآءَتۡ قِيلَ أَهَٰكَذَا عَرۡشُكِۖ قَالَتۡ كَأَنَّهُۥ هُوَۚ وَأُوتِينَا ٱلۡعِلۡمَ مِن قَبۡلِهَا وَكُنَّا مُسۡلِمِينَ ﴿٤٢﴾ وَصَدَّهَا مَا كَانَت تَّعۡبُدُ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ إِنَّهَا كَانَتۡ مِن قَوۡمٖ كَٰفِرِينَ ﴿٤٣﴾ قِيلَ لَهَا ٱدۡخُلِي ٱلصَّرۡحَۖ فَلَمَّا رَأَتۡهُ حَسِبَتۡهُ لُجَّةٗ وَكَشَفَتۡ عَن سَاقَيۡهَاۚ قَالَ إِنَّهُۥ صَرۡحٞ مُّمَرَّدٞ مِّن قَوَارِيرَۗ قَالَتۡ رَبِّ إِنِّي ظَلَمۡتُ نَفۡسِي وَأَسۡلَمۡتُ مَعَ سُلَيۡمَٰنَ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ﴿٤٤﴾

41. (Sai Sulaimanu) ya ce: "Ku sauya kamannin gadon nata mu gani za ta gane (shi) ko kuwa za ta zamanto cikin waɗanda ba sa ganewa?"

42. To lokacin da ta zo, sai aka ce (da ita): "Shin haka kuwa gadonki yake?" Sai ta ce: "Sai ka ce shi." (Sulaimanu ya ce): "An kuwa ba mu ilimi tun gabaninta, kuma mun kasance Musulmi.

43. "Kuma abin da ta kasance tana bauta wa ba Allah ba, shi ya hana ta (yin imani); lalle ita ta kasance cikin mutane kafurai."

44. Aka ce da ita: "Ki shiga fadar;" to lokacin da ta gan ta sai ta zace ta ruwa ne mai zurfi, sai kuwa ta yaye ƙwaurinta. Sai (Sulaimanu) ya ce: "Ai ita fada ce da aka gina da gogaggun kasaken ƙarau (ruwa yake gudana ta ƙarƙashinsu)." Ta ce: "Ya Ubangijina, haƙiƙa na zalunci kaina, na kuma miƙa wuya ga Allah Ubangijin talikai tare da Sulaimanu."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ga gadon Sarauniya a gabansa, sai ya umarci masu gudanar da lamarin fada da cewa su sauya kamannin gadon ta hanyar ƙara masa wasu abubuwa da ba ya da shi ko rage masa wasu domin yana so ne ya auna kaifin basirarta ya ga cewa za ta gane nata ne ko ba za ta iya ganewa ba.
Bayan isowar Sarauniya fadar Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai ta ga gadon sarauta a gabanta wanda ya yi kama da nata, to amma a iya saninta ta baro nata a ƙasarta, daga nan sai aka tambaye ta cewa shin gadonta kamar wannan yake? Sai ta amsa da cewa: "Kamar dai shi."
Da Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ga kaifin basirarta da zurfin hankalinta sai ya bayyana girman ni'imar da Allah ya yi masa wadda ta zarce irin abin da Allah ya ba ta na hankali da ganewa.

Ya bayyana cewa Allah ya ba shi ilimi tun gabanin a ba ta wanda kuma ya fi nata, domin nasa ilimin annabta ne, sannan kuma ga shi Musulmi ne tun da farko, ita kuma kafira mai bautar rana ba Allah ba, bautar da ta hana ta ita da mutanenta su yi imani da Allah su bauta masa shi kaɗai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi niyyar ya nuna wa Sarauniya ƙasaitaccen mulkin da Allah ya ba shi, don haka ya kirawo ta don ya nuna mata fadarsa, aka yi mata iso ta shigo sai ta ga ai wani wuri ne kamar ruwa mai zurfi za ta shiga, sai kawai ta yaye ƙwaurinta don kada tufafinta su jiƙe da ruwa. Sai Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sanar da ita cewa wannan da take gani ba ruwa ne a kwance ba; fada ce da aka gina ta da gogaggun kasaken ƙarau waɗanda ruwa yake gudana ta ƙarƙashinsu, don haka ba sai ta yaye ƙwaurinta ba. To ɗokacin da ta ga abin da ta gani na mamaki da girman mulki da ƙasaitar iko, ta kuma fahimci cewa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba wai sarki ne ba kawai; annabin Allah ne, sai ta bayyana tubanta ga Allah ta kuma musulunta a hannun Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babbar manufar aiko da annabawa ita ce kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, watau bin hanyar Tauhidi.

2. Neman gafara wajen Allah, kuma shi ne sanadiyyar samun rahamar Allah.

3. Camfi ba ɗabi'ar mutanen ƙwarai ba ne.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana jarraba bayinsa ne da kyakkyawan abubuwa da kuma mummuna.

Suratun Namli (45-47)
وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَآ إِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمۡ صَٰلِحًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ فَإِذَا هُمۡ فَرِيقَانِ يَخۡتَصِمُونَ ٤٥ قَالَ يَٰقَوۡمِ لِمَ تَسۡتَعۡجِلُونَ بِٱلسَّيِّئَةِ قَبۡلَ ٱلۡحَسَنَةِۖ لَوۡلَا تَسۡتَغۡفِرُونَ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٤٦ قَالُواْ ٱطَّيَّرۡنَا بِكَ وَبِمَن مَّعَكَۚ قَالَ طَٰٓئِرُكُمۡ عِندَ ٱللَّهِۖ بَلۡ أَنتُمۡ قَوۡمٞ تُفۡتَنُونَ ٤٧

45. Haƙiƙa kuma Mun aiko wa Samudawa ɗan'uwansu Salihu da cewa: "Ku bauta wa Allah," sai ga su sun rabu ƙungiyoyi biyu suna jayayya.

46. Ya ce: "Ya ku mutanena, don me kuke neman gaggautowar mummunan sakamako tun gabanin kyakkyawa? Don me ba za ku nemi gafarar Allah ba don a ji ƙan ku."

47. Sai suka ce: "Mu mun camfa ka kai da waɗanda suke tare da kai." Sai ya ce: "Camfinku na ga Allah. A'a, ku dai mutane ne da ake jarraba ku."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo wani ɓangare na labarin Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da ya aike shi zuwa ga ƙabilarsa Samudawa waɗanda suke bautar gumaka ba Allah ba. Ya umarce su da su bauta wa Allah shi kaɗai su bar bautar gumaka, sai ga shi sun kasu ƙungiya biyu;
• Kungiya ta farko su ne waɗanda suka ba da gaskiya da Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka yarda su bauta wa Allah shi kaɗai.
• Kungiya ta biyu su ne waɗanda suka ƙaryata Annabi Salihu suka kafirce wa Allah. Waɗannan kuma su ne suka fi yawa.

Kungiyoyin biyu suka shiga jayayya da juna, kowa yana cewa shi ne a kan gaskiya.Annabi Salihu ya yi ta bin Samudawa da lalama tare da nuna musu haɗarin abin da suke kai na shirka da Allah wanda zai iya jawo musu hallaka kamar yadda aka hallakar da waɗanda suka gabace su kamar Adawa.
To amma wannan bai sa sun saurare shi ba, sai ma tsaurin kansu ne ya ƙaru har suka fara nemansa da ya kawo musu azabar da yake ta tsoratar da su da ita idan har shi mai gaskiya ne.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da jan hankalin mutanensa da cewa bai dace su riƙa gaggauto wa kawunansu uƙubar Allah ba wadda idan har ta sauka ba za ta yi musu kyau ba, a maimakon su nemi rahamar Allah ta hanyar yin imani da aikata kyawawan ayyuka, su nemi gafarar Allah su tuba su bar abin da suke a kai na shirka da saɓon Allah, don Allah ya ji ƙan su ya yafe musu laifukansu na baya da suka yi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mutanen Annabi Salihu sun bijire wa wannan nasiha da wa'azi da ya yi musu har ma sai suka shiga zargin sa shi da waɗanda suka ba da gaskiya da shi suna camfa su da cewa su ne sanadiyyar faruwar wasu matsaloli na rayuwa da suke fuskanta. Sai Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya amsa musu da cewa duk wani camfi da za su yi a kan musibun da suke samun su Allah yana sane da haka, kuma wannan wata jarraba ce daga Allah saboda zunubansu da kafircinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda yake shirya wa mutanen kirki mummunan tanadi, to ba zai kai labari ba, domin ba zai yi kyakkyawan ƙarshe ba.

2. A ko'ina ana samun gungun mutane 'yan ta'adda da babu niyyar alheri ko kaɗan tare da su in ban da tunanin yadda za su yi ɓarna a bayan ƙasa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana kare masoyansa daga makirce-makircen maƙiyansu ba tare da sun sani ba.

4. A cikin wannan ƙissa akwai ƙaƙƙarfan kashedi ga mushirikan Makka waɗanda suke ƙulle-ƙullen makircin yadda za su gama da Annabi (ﷺ) da nuna musu ƙarshen al'amarin makircin mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) gare shi. To su ma in ba su hanu ba za su yi mummunan ƙarshe irin na waɗannan.

5. Zalunci kowane iri ne yana tare da mummunan haɗari a rayuwar ɗan'adam.

6. Imani da taƙawa su ne hanyar samun tsira daga duk wani abin ƙi duniya da lahira.

Suratun Namli (48-53)
وَكَانَ فِي ٱلۡمَدِينَةِ تِسۡعَةُ رَهۡطٖ يُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا يُصۡلِحُونَ ٤٨ قَالُواْ تَقَاسَمُواْ بِٱللَّهِ لَنُبَيِّتَنَّهُۥ وَأَهۡلَهُۥ ثُمَّ لَنَقُولَنَّ لِوَلِيِّهِۦ مَا شَهِدۡنَا مَهۡلِكَ أَهۡلِهِۦ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ٤٩ وَمَكَرُواْ مَكۡرٗا وَمَكَرۡنَا مَكۡرٗا وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٥٠ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ مَكۡرِهِمۡ أَنَّا دَمَّرۡنَٰهُمۡ وَقَوۡمَهُمۡ أَجۡمَعِينَ ٥١ فَتِلۡكَ بُيُوتُهُمۡ خَاوِيَةَۢ بِمَا ظَلَمُوٓاْۗ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ٥٢ وَأَنجَيۡنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ٥٣

48. A cikin birnin kuma akwai wani gungu na mutum tara waɗanda suke ɓarna a bayan ƙasa kuma ba sa gyara.

49. Sai suka ce: “Mun rantse da Allah a junanmu cewa lalle za mu kashe shi cikin dare shi da iyalinsa, sannan za mu faɗa wa mai neman jininsa cewa, ba mu halarci wurin kashe iyalinsa ba, kuma lalle mu masu gaskiya ne.”

50. Kuma suka shirya makirci, Mu kuma Muka shirya rusa makircinsu alhali kuwa su ba su sani ba.

51. Sai ka duba ka ga yadda ƙarshen makircinsu ya zama, watau Mun hallakar da su tare da mutanensu baki ɗaya.

52. To ga gidajensu can a rugurguje babu ƙowa saboda zaluncinsu. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga mutanen da suke ganewa.

53. Muka kuma tserar da waɗanda suka yi imani, suka kuma ƙasance suna kiyaye dokokin Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da mu cewa a garin Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), watau Hijiru akwai gungun wasu mazaje su tara waɗanda in ban da ɓarna a bayan ƙasa babu abin da suka sa a gaba. Ƙo kaɗan ba su da niyyar kawo gyara ko goyon bayansa. Sai suka ɗaura ɗamarar yaƙi da Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da da’awarsa da addininsa. Waɗannan mutane sun haɗu sun tattauna suka kuma yi rantsuwa a junansu cewa lallai za su far ma Annabi Salihu cikin dare su ƙashe shi tare da iyalansa. Sannan idan masu bin kadin jininsa sun fito suna neman a ɗaukar musu fansa, to za su fito su ƙeƙasa ƙasa su rantse cewa su ba su ma san wanda ya yi kisan ba, kuma ba shakka su iya gaskiyarsu suke faɗa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa sun shirya makircinsu na kashe Annabi Salihu da iyalansa a ɓoye ko da mutanensu kafirai ba su faɗa wa ba, to amma shi ma Allah ya shirya yadda zai ruguza makircinsu ya kare Annabi Salihu da iyalansa har da mabiyansa ya kuma hallaka maƙiyansa kafirai ba tare da sun san da haka ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa ya duba ya ga yadda ƙarshen makircin waɗancan maɓarnata ‘yan ta’adda ya zamo, watau shin sun yi nasara ko kuma Allah ya wargaza lamarinsu? Allah ya bayyana cewa tabbas ya hallakar da su gaba ɗaya, domin ya sauko musu da wata tsawa ta azaba wadda ta gama da su baki ɗaya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya nuna cewa ga gidajensu can a rugurguje, katangunsu sun faɗi, rufinsu ya ɗauke, fayau babu ƙowa a cikinsu saboda zaluncinsu da shirkarsu da Allah. Lalle a cikin hallakar da waɗannan kafirai akwai izina ga mutane masu gane haƙiƙanin al’amura yadda suke.
Allah kuma ya tabbatar da cewa ya tserar da mutanen da suka yi imani da Allah da Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuma suka zamanto suna kiyaye dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Neman maza da sha’awa babu saɓon Allah da ya yi muninsa. Duk wani mai hankali zai gane shi ya ƙyamace shi.

2. Idan mutane sun jahilci Allah da girmansa da haɗarin saɓa masa, to babu irin laifin da ba za su iya afkawa cikinsa ba.

3. Idan mutane suka riga suka dulmiya cikin kafirci da saɓon Allah, to sai ka same su suna guje wa tsarkakan mutane, suna fifita ƙazanta a kan tsarki.

4. Wani lokaci Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan matsi bakin marar gaskiya har ya furta gaskiyar da yake guje mata da kansa, kamar yadda Allah ya matsi bakin mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka danganta shi da iyalansa zuwa ga tsarki, wanda hakan yana nuna su sun riga sun dulmiya cikin ƙazanta ba za su iya fitowa ba.

5. Marasa gaskiya sukan koma ga amfani da ƙarfi yayin da suka fuskanci an ƙure su ta fuskar hujja da dalilai.

6. Alaƙa ta auratayya ba za ta amfani mutum ba a wurin Allah idan babu imani.

Suratun Namli (54-58)

وَلُوطًا إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ أَتَأْتُونَ ٱلْفَٰحِشَةَ وَأَنتُمْ تُبْصِرُونَ ﴿٥٤﴾ أَئِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلرِّجَالَ شَهْوَةً مِّن دُونِ ٱلنِّسَآءِۚ بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ تَجْهَلُونَ ﴿٥٥﴾ ۞ فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓا۟ أَخْرِجُوٓا۟ ءَالَ لُوطٍ مِّن قَرْيَتِكُمْ ۖ إِنَّهُمْ أُنَاسٌ يَتَطَهَّرُونَ ﴿٥٦﴾ فَأَنجَيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥٓ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ قَدَّرْنَٰهَا مِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿٥٧﴾ وَأَمْطَرْنَا عَلَيْهِم مَّطَرًا ۖ فَسَآءَ مَطَرُ ٱلْمُنذَرِينَ ﴿٥٨﴾

54. Kuma ka (ambaci) Luɗu lokacin da ya ce da mutanensa: “Yanzu kwa riƙa zaike wa alfasha alhali kuwa kuna gani?

55. “Yanzu kwa riƙa zaike wa maza don sha’awa ba mata ba? A’a, ku dai wasu irin mutane ne da kuke da jahilci”.

56. To babu wata amsa da ta fito daga bakin mutanensa sai kawai suka ce: “Ku fitar da Luɗu shi da iyalinsa daga alƙaryarku; lalle su mutane ne da suke nuna su masu tsarki ne.”

57. Sai Muka tserar da shi tare da iyalinsa in ban da matarsa da Muka ƙaddara ta cikin hallakakku.

58. Muka kuma yi musu ruwan azaba; to ruwan azabar waɗanda aka yi wa gargaɗi ya munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya aike shi zuwa ga alƙaryar Sadum inda mutanen garin suka shahara da wata mummunar al’ada ta neman maza da sha’awa, mugun aikin da ba a taɓa samun masu yin irinsa ba gabaninsu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ja hankalinsu da cewa, yanzu sa riƙa aikata wannan mummunan aiki alhalin suna ganin muninsa a zahiri kuma suna sane, amma toshewar basira ta sa sun ƙi dainawa? Ya fito ƙarara ya bayyana musu abin da yake nufi da maganarsa, watau neman maza da sha’awa maimakon mata da Allah ya halatta musu su neme su ta hanyar aure amma suka tubure su sai dai maza. Ya tabbatar da cewa su mutane ne da jahilci ya yi wa katutu, don haka ba su san komai daga abin da ya wajaba a kansu na imani da tsarkaka daga saɓon Allah ba.
Bayan Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gargaɗi mutanensa ya yi musu nasiha sun ƙi ba shi wata amsa da ke nuna sun yarda da wa’azinsa sun karɓi nasiharsa, sai ma kawai suka shiga kiraye-kirayen junansu cewa su haɗu su kori Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da iyalansa da mabiyansa daga garinsu, domin wai su mutane ne da suke tsarkake kansu daga neman maza.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da iyalansa, in ban da matarsa da Allah ya riga ya ƙaddara tana cikin halakakku. Amma bai halakar da su ba sai da ya aiki mala’iku suka zo wurin Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cikin kamanni na wasu baƙi. Da mutanen gari suka ji labarin zuwansu, sai suka yo tururuwa zuwa gidan Annabi Luɗu da niyyar aikata

mummunan aiki da baƙinsa. Annabi Luɗu ya ƙulle ƙofar gidansa, al'amari ya tsananta gare shi. Amma mala'ikun nan suka sanar da shi cewa su ba mutane ba ne, mala'iku ne, sun zo da nufin tserar da shi da iyalansa daga wannan gari, domin asuba na yi za su hallaka mutanen alƙaryar baki ɗaya. Suka umarce shi ya fita tare da iyalansa cikin dare, amma matarsa ita ma tana daga cikin waɗanda za a hallakar, domin tana tare da mutanen gari a kan kafirci, ba ta yi imani da shi ba. Annabi Luɗu da iyalansa kuwa suka fita cikin dare suka tsira, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mala'ikun nan suka ɓaɓɓake wannan gari kacokam da duk abin da yake cikinsa suka ɗaga shi can ƙololuwar sama sannan suka kifar da shi, samansa ta koma ƙasa, sannan aka bi su da ruwan duwatsu na azaba. Allah ya tabbatar da cewa ruwan azabar da aka yi wa waɗanda aka yi wa gargaɗi suka ƙi ji ya munana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da aƙidar Tauhidi da dasa ta a zukata ta hanyar tunatarwa a kan ni'imomin Allah.

2. Wajabcin gode wa Allah a kan ni'imominsa na fili da na ɓoye.

3. Roƙa wa annabawa amincin Allah a gare su.

4. Shirkar mushirkan Larabawa ita ce daidaita Allah da gumakansu wajen bauta.

5. Tabbatar da aƙidar Tauhidi ta hanyar kawo dalilai bayyanannu da ke cikin halittun da Allah ya yi a sama da ƙasa.

6. Allah ya yi alƙawari ga wanda ya shiga halin matsuwa zai karɓi addu'arsa idan ya roƙe shi da ikhlasi, mumini ne shi ko kafiri.

7. Ubaidullahi ɗan Abu Salihu ya ce: Wata rana Ɗawus (almajirin Ibn Abbas (Allah ya kara masa yarda)) ya zo duba ni ina rashin lafiya, sai na ce masa: "Ya baban Abdurrahman, ka yi mini addu'a." Sai ya ce: "Ka yi wa kanka addu'a, domin shi Allah yana amsa addu'ar wanda yake cikin matsuwa idan ya roƙe shi." [*Ibn Kasir*, Juzu'i na 6, shafi na 204].

Suratun Namli (59-64)

قُلِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ وَسَلَٰمٌ عَلَىٰ عِبَادِهِ ٱلَّذِينَ ٱصۡطَفَىٰٓۗ ءَآللَّهُ خَيۡرٌ أَمَّا يُشۡرِكُونَ ٥٩ أَمَّنۡ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَأَنزَلَ لَكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَنۢبَتۡنَا بِهِۦ حَدَآئِقَ ذَاتَ بَهۡجَةٖ مَّا كَانَ لَكُمۡ أَن تُنۢبِتُواْ شَجَرَهَآۗ أَءِلَٰهٞ مَّعَ ٱللَّهِۚ بَلۡ هُمۡ قَوۡمٞ يَعۡدِلُونَ ٦٠ أَمَّن جَعَلَ ٱلۡأَرۡضَ قَرَارٗا وَجَعَلَ خِلَٰلَهَآ أَنۡهَٰرٗا وَجَعَلَ لَهَا رَوَٰسِيَ وَجَعَلَ بَيۡنَ ٱلۡبَحۡرَيۡنِ حَاجِزًاۗ أَءِلَٰهٞ مَّعَ ٱللَّهِۚ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٦١ أَمَّن يُجِيبُ ٱلۡمُضۡطَرَّ إِذَا دَعَاهُ وَيَكۡشِفُ ٱلسُّوٓءَ وَيَجۡعَلُكُمۡ خُلَفَآءَ ٱلۡأَرۡضِۗ أَءِلَٰهٞ مَّعَ ٱللَّهِۚ قَلِيلٗا مَّا تَذَكَّرُونَ ٦٢ أَمَّن يَهۡدِيكُمۡ فِي ظُلُمَٰتِ ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِ وَمَن يُرۡسِلُ ٱلرِّيَٰحَ بُشۡرَۢا بَيۡنَ يَدَيۡ رَحۡمَتِهِۦٓۗ أَءِلَٰهٞ مَّعَ ٱللَّهِۚ تَعَٰلَى ٱللَّهُ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٦٣ أَمَّن يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَمَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۗ أَءِلَٰهٞ مَّعَ ٱللَّهِۚ قُلۡ هَاتُواْ بُرۡهَٰنَكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٦٤

59. Ka ce: "Yabo ya tabbata ga Allah, kuma aminci ya tabbata ga bayinsa waɗanda Ya zaɓa." Yanzu Allah ne Ya fi ko kuwa abin da suke tarawa (da Shi)?

60. Ko kuwa wane ne ya halicci sammai da ƙasa, ya kuma saukar muku da ruwa daga sama, sannan Muka tsirar da (shukokin) gonaki masu ƙayatarwa, ba kuwa za ku iya tsirar da bishiyoyinsu ba? Shin akwai wani abin bauta na gaskiya tare da Allah? A'a, su dai mutane ne da suke kauce wa gaskiya.

61. Ko kuwa wane ne ya sanya ƙasa wurin zama, ya kuma sanya ƙoramu a tsattsakinta, kuma ya sanya mata turaku, kana kuma ya sanya shamaki tsakanin kogunan nan biyu (na ruwan daɗi da na ruwan zartsi)? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah? A'a, yawancinsu dai ba sa ganewa.

62. Ko kuwa wane ne yake amsa wa wanda yake cikin matsuwa lokacin da ya roƙe shi, yake kuma yaye duk wani bala'i, yake kuma sanya ku halifofi a bayan ƙasa? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah? Kaɗan ne ƙwarai kuke wa'azantuwa.

63. Ko kuwa wane ne yake shiryar da ku a cikin duffan tudu da na kogi, kuma wane ne yake sako iska tana mai bushara gabanin (saukar) rahamarsa? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah? Allah Ya ɗaukaka daga abin da suke tara (Shi da shi).

64. Ko kuwa wane ne yake ƙagar halitta sannan ya dawo da ita (bayan mutuwa), kuma wane ne yake arzuta ku ta sama da ƙasa? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah?" Ka ce (da su): "Ku kawo dalilinku idan kun kasance masu gaskiya."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya tabbatar masa dukkan siffofi na yabo da godiya bisa ni'imominsa ga bayinsa, da kuma amincin da ya ba wa bayinsa waɗanda ya zaɓa ya kuɓutar da su daga azabar duniya wadda ya halakar da maƙiyansa da ita. Sannan ya ƙalubalance su da cewa yanzu Allah ne ya fi ko kuwa abin da suke shirka da shi wanda ba ya tsinana musu wani amfani ko ya magance musu wata cuta?
Allah kuma ya yi bayanin wasu ayyukansa waɗanda ya keɓanta da su masu nuna cikar Kudurarsa da ƙarfin ikonsa don tabbatar da Kaɗaitarsa wajen bauta. Allah ya ci gaba da tambayar mushirikai masu bautar waninsa da cewa, wane ne ya halicci sammai da ƙasa ba tare da ya kwaikwaya daga wurin wani ba, ya kuma saukar wa da mutane ruwa daga sama ya fitar musu da shukokin gonaki masu kyau da ban sha'awa da shi, yayin da su mutane ba za su iya fitar da bishiyoyin waɗannan gonaki ba domin gazawarsu, amma kuma sun san Allah ne ya yi musu wannan baiwa? To shin akwai wani abin bauta tare da Allah wanda shi ma zai iya waɗannan ayyuka har ya cancanci a bauta masa tare da Allah? Allah ya tabbatar da cewa babu, su dai mushirikai kawai mutane ne da suke kauce wa gaskiya, suke kuma daidaita wasu da Allah ba tare da wata hujja ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tambayar su cewa, wane ne ya sanya ƙasa ta zama mazauni ga bayinsa, su gina gidajen zama a kanta su kuma yi shuke-shuke da kai-komonsu a kanta ba tare da tana tangal-tangal da su ba, ya kuma sanya ƙoramu suna gudana a tsakankaninta domin mutane da dabbobi su amfana, ya kuma kafa duwarwatsu a kanta don zama turaku masu hana ta motsi, ya kuma sanya shamaki tsakanin koguna guda biyu, na ruwan daɗi da na ruwan zartsi, ta yadda ba za su gauraya da juna ba, ruwan da mutane za su sha ya lalace su rasa ruwan sha? Ya tambaye su cewa, shin akwai wani abin bauta na gaskiya tare da Allah wanda zai iya yin waɗannan ayyuka da har za a daidaita shi da Allah a bauta masa tare da shi? Sai Allah ya tabbatar da cewa babu, yawancinsu ba su da sani ne, suna dai bin iyayensu ne da shugabanninsu ido rufe.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sake tambayar su cewa, wane ne yake amsa addu'ar wanda ya shiga wata matsuwa idan ya roƙe shi, ya yaye masa duk wani mummunan abu da zai same shi na rashin lafiya da talauci da makamantansu?

An karɓo daga wani mutum daga ƙabilar Balhujaim ya ce: Na ce: “Ya Manzon Allah zuwa ga me kake kira?” Ya ce: “Ina kira ne zuwa ga Allah shi kaɗai wanda idan wata cuta ta same ka ka roƙe shi sai ya yaye maka, wanda kuma idan ka ɓace a ƙungurmin jeji ka roƙe shi sai ya dawo da kai hanya, wanda kuma idan fari ya same ka ka roƙe shi sai ya fito maka da shuka.” Mutumin nan ya ce: Sai na ce: “To yi mini wasiyya.” Sai ya ce: “Kada ka kuskura ka zagi wani, kada kuma ka guje wa aikin alheri ko da kuwa ka haɗu da ɗan’uwanka ne kana yi masa fara’a, ko da kuwa ka zuba ruwa ne daga gugarka a cikin ƙoƙon mai neman ruwan sha, ka kuma sanya kwarjallenka zuwa rabin ƙwauri, idan ka ƙi to zuwa idanuwan ƙafa. Ka guji sakin kwarjallenka yana jan ƙasa, domin barin kwarjalle yana jan ƙasa yana daga cikin girman kai, Allah kuwa ba ya son girman kai.” [Ahmad #20636].

Wane ne kuma yake mayar da mutane halifofi a bayan ƙasa; wasu su shuɗe wasu su zo su gaje su, tsareku bayan tsareku? Allah ya tambaye su cewa, shin akwai wani abin bauta tare da Allah da yake tarayya da shi a kan waɗannan ayyuka? Sam babu shi. Allah ya tabbatar da cewa kaɗan ne ƙwarai suke wa’azantuwa ko suke ɗaukan izina,

Sai kuma har wa yau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tambayar su cewa, wane ne yake shiryar da su ya nuna musu hanya lokacin da suke tafiya a cikin duffan tudu da na kogi ta hanyar alamu da taurari da ya sanya musu har su samu su tsira daga hallaka? Wane ne kuma yake aiko musu da iska don ta zama albishir gabanin ya saukar musu da rahamarsa, watau ruwan sama wanda rahamar Allah ne ga bayinsa? Allah ya tambaye su cewa, yanzu akwai wani abin bauta tare da Allah wanda yake yi musu waɗannan ayyuka da har ya cancanci su bauta masa? Allah ya ɗaukaka ya kuma tsarkaka daga duk abin da suke yi masa shirka da shi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sake tambayar mushirikai cewa, wane ne yake ƙirƙirar halitta, ya ƙage ta daga babu, sannan kuma ya dawo da ita bayan mutuwa domin hisabi? Kuma wane ne yake arzuta mutane daga sama da ƙasa ta hanyar saukar musu da ruwan sama ya fitar musu da tsirrai daga ƙasa? Shin akwai wani abin bauta tare da Allah wanda zai iya yin waɗannan abubuwan da aka ambata? Sai kuma ya neme su da su kawo hujjojinsu da dalilansu a kan abin da suke faɗa na tarayyar ababen bautar tare da Allah, in dai har suna da gaskiya, domin ita gaskiya ana tabbatar da ita ne ta hanyar hujja da dalili ba ta hanyar da’awar baka kaɗai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ne kaɗai ya san gaibu. Mala’iku a sama da mutane a ƙasa babu wanda ya san gaibu sai abin da Allah ya ga dama ya sanar da wanda ya ga dama.

2. Babu wani mala’ika a sama ko wani annabi ko wani salihi a ƙasa da ya san yaushe ne ranar alƙiyama sai Allah shi kaɗai.

3. Kafirai masu ƙaryata tashin alƙiyama ba su da wata hujja mai ƙarfi in ban da kawai abin da suka gada daga iyayensu da kakanninsu.

Suratun Namli (65-66)

قُل لَّا يَعۡلَمُ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ ٱلۡغَيۡبَ إِلَّا ٱللَّهُۚ وَمَا يَشۡعُرُونَ أَيَّانَ يُبۡعَثُونَ ٦٥ بَلِ ٱدَّٰرَكَ عِلۡمُهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِۚ بَلۡ هُمۡ فِي شَكّٖ مِّنۡهَاۖ بَلۡ هُم مِّنۡهَا عَمُونَ ٦٦

65. Ka ce (da su): “Duk wanda yake cikin sammai da ƙasa in ba Allah ba ba wanda ya san gaibu. Su kuma ba su san lokacin da za a tashe su ba.”

66. A’a, iliminsu game da ranar lahira ya bibiyi na junansu ne. Ba ma wannan kaɗai ba, hakanan suna cikin kokwanto ne game da ita. Ban da hakan ma, su dai makafi ne game da ita.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tabbatar da cewa babu wani a cikin sammai da ƙasa da ya san gaibu sai Allah shi kaɗai.

An karɓo daga A’isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: “Duk wanda ya riya cewa Annabi (ﷺ) ya san abin da zai kasance gobe, to haƙika ya yi wa Allah ƙarya babba, Allah yana cewa: “Ka ce: “Duk wanda yake cikin sammai da ƙasa in ban da Allah babu wanda ya san gaibu.” [Muslim #177].

Hakanan duk waɗanda suke sama da ƙasa babu wanda ya san yaushe ne za a tashi mutane domin hisabi da sakamako sai Allah kaɗai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da jahilcin mushirikai masu ƙaryata ranar lahira game da ita, ya bayyana cewa iliminsu game da sha’anin lahira ya bibiyi na junansu ne, watau sun sami iliminsu game da ita daga iyayensu, su ma daga nasu iyayen, watau abin da ya shahara a wajensu na ƙaryata ranar alƙiyama. Allah ya nuna ba wannan kaɗai ba ma, a’a suna ma cikin shakku da ruɗu game da lahirar, kai haƙika idanunsu ma sun makance ne ba sa ganin kowace irin hujja da take tabbatar da zuwan ranar lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirai sun ƙaryata tashin mutane bayan mutuwa saboda ba su ɗauki cikakkiyar Kudurar Allah da ikonsa a bakin komai ba.

2. Bibiyar labarin mutanen farko da gane wa ido wuraren da aka hallaka masu ƙaryata manzanni don samun izina da wa’azi daga gare su.

3. Annabi (ﷺ) mutum ne mai tsananin tausaya wa al’ummarsa da jin ƙan su, duk sa’adda zai ji alƙawarin narko a kansu daga wajen Allah sai wannan tausayin nasa ya motsa, shi ne ya sa Allah yake nutsar masa da zuciya, ya sanya masa juriya da dakewa da nuna masa kada ya yi baƙin ciki game da azabar da za ta same su idan sun ƙi yin imani.

4. Ni’imomin Allah da falalarsa masu yawa ne a kan mutane sai dai yawancinsu butulu ne ba sa gode wa Allah a kan waɗannan ni’imomin. Don haka rashin godiya ga Allah ɗabi’a ce ta kafirai.

5. Ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kewaye ɗaukacin komai da komai.

Suratun Namli (67-75)
وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَءِذَا كُنَّا تُرَٰبًا وَءَابَآؤُنَآ أَئِنَّا لَمُخۡرَجُونَ ٦٧ لَقَدۡ وُعِدۡنَا هَٰذَا نَحۡنُ وَءَابَآؤُنَا مِن قَبۡلُ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٦٨ قُلۡ سِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٦٩ وَلَا تَحۡزَنۡ عَلَيۡهِمۡ وَلَا تَكُن فِي ضَيۡقٖ مِّمَّا يَمۡكُرُونَ ٧٠ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٧١ قُلۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ رَدِفَ لَكُم بَعۡضُ ٱلَّذِي تَسۡتَعۡجِلُونَ ٧٢ وَإِنَّ رَبَّكَ لَذُو فَضۡلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَشۡكُرُونَ ٧٣ وَإِنَّ رَبَّكَ لَيَعۡلَمُ مَا تُكِنُّ صُدُورُهُمۡ وَمَا يُعۡلِنُونَ ٧٤ وَمَا مِنۡ غَآئِبَةٖ فِي ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٍ ٧٥

67. Waɗanda suka kafirta, kuma suka ce: “Yanzu bayan mun zama ƙasa mu da iyayenmu, ashe lalle za a (sake) fito da mu?

68. “Haƙiƙa an yi mana alƙawarin wannan mu da iyayenmu tun a da can, wannan ba komai ba ne face tatsuniyoyin mutanen farko.”

69. Ka ce (da su): “Ku yi tafiya a bayan ƙasa za ku ga yadda ƙarshen kafurai ya kasance.”

70. Kuma kada ranka ya ɓaci game da su, kada kuma ka zama cikin ƙuncin zuciya game da makircin da suke ƙullawa.

71. Suna kuma cewa: “Yaushe ne lokacin wannan wa’adin idan kun kasance masu gaskiya?”

72. Ka ce (da su): “Lalle sashin abin da kuke gaggauto da zuwansa (na azaba) ya kusanto.”

73. Kuma lalle Ubangijinka Mai falala ne ga mutane, sai dai kuma yawancinsu ba sa godewa.

74. Lalle kuma Ubangijinka tabbas Yana sane da abin da zukatansu suke ɓoyewa, da kuma abin da suke bayyanawa.

75. Kuma babu wani abu da yake ɓoye a cikin sammai da ƙasa face yana cikin littafi mabayyani (watau Lauhul-Mahafuzu).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai suke jayayya a kan tabbatar ranar alƙiyama har ma suke cewa babu yadda za a yi a tashe su ballantana iyayensu da rai bayan sun mutu sun zama ƙasa, kuma da man can an daɗe ana yi musu wannan alƙawari su da iyayensu, ga shi an kawo yanzu abin da ake faɗa musu bai auku ba, saboda haka ne wai suka tabbatar da cewa duk maganganun da ake faɗa musu game da zuwan ranar alƙiyama ba komai ba ne in ban da tatsuniyoyin mutanen da.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya faɗa musu cewa su yawata ko’ina a bayan ƙasa su ga yadda ƙarshen masu manyan laifuffuka irin nasu ya kasance, watau duk Allah ya hallakar da su saboda ƙaryata annabawansu da suke yi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) nasiha da ya daina ɓata ransa a kansu don ganin sun bijire wa da’awarsa; kada ya nuna damuwarsa a kan haka, Allah zai taimake shi a kansu, ya mayar da makircinsu ya koma musu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tambayar da mushirikai suke yi wa Manzon Allah (ﷺ) game da tashin alƙiyama da cewa, wai yaushe ne ranar za ta zo idan har yana da gaskiya? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya mayar musu da martani cewa su daina wani zumuɗi domin wani ɓangare na azabar da suke sauraron zuwanta ya kusanto.
Sannan Allah ya tabbatar wa da Annabi cewa shi mai falala ne a kan mutane saboda haka ne ba ya gaggauto musu da azaba duk kuwa da kafircinsu da saɓon Allah da suke ta tafkawa dare da rana. To amma yawancin mutane ba sa gode wa ni’imomin da yake yi musu.Ya kuma bayyana masa cewa lalle ya san ɗaukacin abubuwan da zukatan bayinsa suke ɓoyewa da wanda suke bayyanawa, babu abin da yake ɓoye a gare shi, zai saka musu kuma a kan dukkan ayyukansu.Kuma ya tabbatar da cewa babu wani abu da yake ɓoye a sama da ƙasa wanda mutane ba su san da zamansa ba face yana rubuce a cikin littafi mabayyani, watau Lauhul-Mahfuzu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur’ani littafi ne na gaskiya mai fayyace bayanai a kan abubuwan da Banu Isra’ila suka riƙa saɓani da junansu a kai, kamar sha’anin Maryamu da ɗanta Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Ya kuma

labarta musu gaskiyar al’amura masu yawa waɗanda aka jirkita haƙiƙaninsu a cikin littattafansu, kamar labarin Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Sarauniyar Saba’i.

2. Alƙur’ani rahama ce ga muminai, domin lokacin da suka karɓi shiriyar da ya zo musu da ita sai suka rabauta a duniya zukatansu suka tsarkaka ayyukansu suka gyaru kansu ya haɗu. Sannan kuma a lahira za su dace da babban rabo watau Aljanna.

3. Wanda yake kan gaskiya yake kuma kira zuwa gare ta ya taimaka mata shi ne ya fi kowa cancantar ya dogara ga Allah cikin al’amuransa.

4. Shiriya a hannun Allah take ba a hannun Manzo ba. Allah ne yake shiriyar da wanda ya ga dama.

5. Zahirin Alƙur’ani shi ne kore wa matattu ji, sai waɗanda nassi ya nuna Allah ya jiyar da su bayan mutuwarsu, kamar kafiran da aka kashe a yaƙin Badar, aka jefa gawarwakinsu cikin rijiya. Da Annabi (ﷺ) ya yi magana da su Allah ya jiyar da su maganarsa a lokacin, kamar yadda [Bukhari #3976 da Muslim #7402] suka ruwaito daga Anas ɗan Malik (Allah ya kara masa yarda).

6. Hakanan ya tabbata a hadisi, Manzon Allah (ﷺ) ya tabbatar da cewa idan masu raka jana’iza suka ba da baya mamaci yana jin sautin tafiyar takalmansu. [Dubi, Bukhari #1338 da Muslim #7395].

Suratun Namli (76-81)
إِنَّ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ يَقُصُّ عَلَىٰ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ أَكۡثَرَ ٱلَّذِي هُمۡ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ٧٦ وَإِنَّهُۥ لَهُدٗى وَرَحۡمَةٞ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ ٧٧ إِنَّ رَبَّكَ يَقۡضِي بَيۡنَهُم بِحُكۡمِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡعَلِيمُ ٧٨ فَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۖ إِنَّكَ عَلَى ٱلۡحَقِّ ٱلۡمُبِينِ ٧٩ إِنَّكَ لَا تُسۡمِعُ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَلَا تُسۡمِعُ ٱلصُّمَّ ٱلدُّعَآءَ إِذَا وَلَّوۡاْ مُدۡبِرِينَ ٨٠ وَمَآ أَنتَ بِهَٰدِ ٱلۡعُمۡيِ عَن ضَلَٰلَتِهِمۡۖ إِن تُسۡمِعُ إِلَّا مَن يُؤۡمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُم مُّسۡلِمُونَ ٨١

76. Lalle wannan Alƙur’anin yana labarta wa Banu-Isra’ila mafi yawan abin da suke saɓani a kansa.

77. Lalle kuma shi (Alƙur’ani) tabbas shiriya ne kuma rahama ce ga muminai.

78. Lalle Ubangijinka zai yi shari’a a tsakaninsu da hukuncinsa. Shi kuwa Mabuwayi ne, Masani.

79. To ka dogara ga Allah; lalle kai kana kan gaskiya mabayyaniya.

80. Lalle kai ba ka iya jiyar da matattu, ba kuma ka iya jiyar da kurame kira lokacin da suka juya suna masu ba da baya.

81. Kuma sannan kai ba za ka iya shiryar da makafi daga ɓatansu ba; ba wanda kake iya jiyarwa sai wanda ya yi imani da ayoyinmu, to waɗannan su ne Musulmi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da gaskiyar Alƙur’ani wanda ya saukar wa Manzonsa (ﷺ), da cewa yana ba wa Banu Isra’ila labarin mafi yawan abin da suke saɓani a cikinsa tare da yi musu bayanin wuraren da suka kauce wa gaskiya. Kuma lalle shi Alƙur’ani shiriya ce da rahama ga muminai masu aiki da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa tabbas shi ne zai yi hukunci na adalci ranar alƙiyama a tsakanin muminai da kafirai da ma’abota littafi, inda zai ji ƙan muminai ya kuma

azabta kafirai. Shi ne Mabuwayi gagara badau wanda babu mai iya rinjayar sa kuma Masani wanda yake tantance tsakanin mai gaskiya da maƙaryaci.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya dogara gare shi cikin dukkan al'amuransa, ya kuma tabbatar masa cewa yana kan gaskiya bayyananna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Manzo (ﷺ) cewa idan har ya sauke nauyin da aka ɗora masa na isar da saƙon Allah ya kuma dogara da Allah a kan haka, to ɓacewar duk wanda ya ɓace ba za ta cutar da shi ba, domin shi ba zai iya jiyar da matattu komai ba, su ne waɗanda zukatansu suka mutu saboda kafirci, hakanan ba zai iya jiyar da kurame kira ba idan sun juya masa baya. Kuma ba zai iya shiryar da makafi waɗanda basirarsu ta toshe suka makance su dawo daga ɓatan da suke kai ba, don haka ya daina damuwa yana baƙin ciki saboda su. Ya bayyana masa cewa masu imani da Allah waɗanda suke miƙa wuya ga umarninsa ne kaɗai zai iya jiyar da su da'awarsa kuma su saurare shi su amfana da abin da yake karanta musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da ɗaya daga cikin manyan alamomin kusantowar tashin alƙiyama, watau fitowar wata dabba mai magana da mutane.

2. An fito musu da dabba daga ƙasa domin a nuna musu yadda Allah yake raya matattu, saboda sun musunta tashi bayan mutuwa. Dabbar tana yi musu magana ne don ta nuna musu cewa lokacin tattara su a yi musu hisabi ya matso.

3. Allah ya ƙaddara dabba ce za ta riƙa magana da su a kan tabbatar da abin da suka ƙaryata, domin hakan ya zama wani nau'i ne na ƙasƙantarwa a gare su saboda sun ƙi karɓar maganar wanda ya fi kowa daraja da fasaha, shi ne Annabi (ﷺ), sun ƙaryata abin da Alƙur'ani ya yi ta sanar da su, to yau ga su dole ne su saurari maganar dabba su kuma gaskata ta; wannan kuma ya zame musu abin kunya a ranar alƙiyama.

Suratun Namli (82-85)
*وَإِذَا وَقَعَ ٱلۡقَوۡلُ عَلَيۡهِمۡ أَخۡرَجۡنَا لَهُمۡ دَآبَّةٗ مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ تُكَلِّمُهُمۡ أَنَّ ٱلنَّاسَ كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا لَا يُوقِنُونَ ٨٢ وَيَوۡمَ نَحۡشُرُ مِن كُلِّ أُمَّةٖ فَوۡجٗا مِّمَّن يُكَذِّبُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُمۡ يُوزَعُونَ ٨٣ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُو قَالَ أَكَذَّبۡتُم بِـَٔايَٰتِي وَلَمۡ تُحِيطُواْ بِهَا عِلۡمًا أَمَّاذَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٨٤ وَوَقَعَ ٱلۡقَوۡلُ عَلَيۡهِم بِمَا ظَلَمُواْ فَهُمۡ لَا يَنطِقُونَ ٨٥

82. Kuma idan lokacin da aka alƙawarta musu ya cika, to za Mu fito musu da wata dabba daga ƙasa da za ta riƙa faɗa musu cewa: "Lalle mutane sun zamanto ba sa sakankancewa da ayoyinmu."

83. Kuma ka tuna ranar da za Mu tattara jama'a na kowacce al'umma, daga cikin waɗanda suke ƙaryata ayoyinmu ana koro su na farko da na ƙarshe.

84. Har yayin da suka zo (sannan Allah) Ya ce da su: "Yanzu ku kuka ƙaryata ayoyina, alhali kuwa ba ku tantance da saninsu ba? Ko kuwa me kuka zamanto kuna aikatawa ne (a duniya)?"

85. Kuma abin da aka alƙawarta musu na azaba ya tabbata a kansu saboda kafircinsu, to su ba za su iya furta komai ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin wata alama daga cikin manyan alamomin tashin alƙiyama ya kuma bayyana wasu abubuwa da za su kasance a ranar hisabi. Watau idan lokacin saukar

azabarsa ya tabbata zai fito wa da mutane wata dabba daga ƙasa da za ta riƙa yi musu magana cewa lalle mutane sun kasance ba sa sakankancewa da ayoyin Allah, watau imaninsu ya yi rauni matuƙa da gaske. Lokacin da wannan dabba za ta bayyana imanin wanda zai yi imani a lokacin ba zai amfane shi ba.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Abubuwa uku idan suka bayyana to imanin wani rai wanda bai yi imani da can ba, ko kuma bai yi aiki na gari ba, ba zai yi masa amfani ba, hudowar rana daga mafaɗarta da bayyanar Dujal da fitowar dabba daga ƙasa." [Muslim #417].

Sannan Allah ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tuna ranar da zai tattara jama'ar manyan mutane daga cikin kowace al'umma na farko da na ƙarshe wuri guda waɗanda suka ƙaryata ayoyinsa sai a gargaɗa su zuwa ga hisabi. Har sai sun iso wajen yi musu hisabi, a nan ne Allah zai tambaye su hujjarsu ta ƙaryata ayoyinsa masu nuna Kaɗaitakarsa suka kuma ƙunshi shari'arsa, alhalin ba wani ilimi ne suka samu ba wanda ya nuna waɗannan ayoyin ƙarya ne. Sannan ya tambaye su abin da suka kasance suna aikatawa a rayuwarsu ta duniya. A nan ne za su tabbatar da kuskuren da suka tafka a duniya, su yi nadamar da ba za ta amfane su da komai ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa azabarsa za ta tabbata a kansu saboda zaluncin da suka yi na kafirce wa Allah da ƙaryata manzanninsa, kuma a wannan ranar ba za su iya buɗa baki su kare kansu ba, kuma ba su da wata hujjar da za su bayar don kuɓutar da kansu daga azaba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Barci da farkawa alamu ne da suke nuna mutuwa da tashi bayan mutuwa.

2. Sassaɓawar dare da rana wata aya ce da ke nuna Kaɗaitakar Allah da cikar Kudurarsa, amma kafirai ba sa lura da ita duk kuwa da kasancewarta tana maimaituwa a gaban idonsu kullum.

3. Tabbatar da busa ta biyu da Mala'ika Israfilu zai yi wadda za ta firgita kowa da kowa sai wanda Allah ya tsare.

4. Imani da kyakkyawan aiki su ne za su sanya mutum ya sami aminta daga firgici da tsoro na busar ranar alƙiyama.

Suratun Namli (86-90)
أَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّا جَعَلۡنَا ٱلَّيۡلَ لِيَسۡكُنُواْ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبۡصِرًاۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٨٦ وَيَوۡمَ يُنفَخُ فِي ٱلصُّورِ فَفَزِعَ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا مَن شَآءَ ٱللَّهُۚ وَكُلٌّ أَتَوۡهُ دَٰخِرِينَ ٨٧ وَتَرَى ٱلۡجِبَالَ تَحۡسَبُهَا جَامِدَةٗ وَهِيَ تَمُرُّ مَرَّ ٱلسَّحَابِۚ صُنۡعَ ٱللَّهِ ٱلَّذِيٓ أَتۡقَنَ كُلَّ شَيۡءٍۚ إِنَّهُۥ خَبِيرُۢ بِمَا تَفۡعَلُونَ ٨٨ مَن جَآءَ بِٱلۡحَسَنَةِ فَلَهُۥ خَيۡرٞ مِّنۡهَا وَهُم مِّن فَزَعٖ يَوۡمَئِذٍ ءَامِنُونَ ٨٩ وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَكُبَّتۡ وُجُوهُهُمۡ فِي ٱلنَّارِ هَلۡ تُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٩٠

86. Yanzu ba sa gani cewa Mu Muka samar da dare don su nutsu a cikinsa, da kuma rana mai haskakawa (don su yi harka)? Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suke yin imani.

87. (Ka tuna) kuma ranar da za a busa ƙaho sai duk mahalukin da yake cikin sammai da ƙasa ya firgita, sai dai wanda Allah Ya toge. Kuma gaba ɗayansu za su zo masa suna masu miƙa wuya.

88. Kuma za ka ga duwatsu ka zaci a tsaye suke cak, alhali kuwa su suna tafiya ne irin tafiyar gizagizai. Aikin Allah kenan wanda Ya kyautata halittar kowane irin abu. Lalle Shi Masanin abin da kuke aikatawa ne.

89. Duk wadanda suka zo da kyakkyawan (aiki), to suna da (lada) fiye da shi, kuma su amintattu ne daga firgitar wannan ranar.

90. Wadanda kuwa suka zo da mummunan (aiki), to an kifar da fuskokinsu cikin wuta, to ba za a saka muku ba sai da irin abin da kuka zamanto kuna aikatawa.

A wadannan ayoyi Allah (Mai tsarki da daukaka) ya jawo hankalin masu karyata tashi bayan mutuwa da cewa ba sa duban barcin da suke yi su farka, shi kansa yana nuna musu yiwuwar tashi bayan mutuwa? Ya kuma bayyana cewa yanzu ba su ga yadda ya samar da dare ba, domin su yi barci su samu natsuwa da hutu, ya kuma sanya rana mai haskawa domin su sami damar gani a cikin yini, su fita su yi harkokinsu na yau-da-kullum? Ya tabbatar musu cewa, a cikin wannan barci da suke yi kullum mai kama da mutuwa da kuma farkawar da suke yi mai kama da tashi bayan mutuwa, lalle akwai ayoyi bayyanannu ga mutane masu imani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da daukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da cewa ya tuna ranar da Mala'ika Israfilu, wanda shi ne aka wakilta shi ya busa kaho domin tashin alkiyama, zai yi busa ta biyu sai duk mahalukin da yake cikin sammai da wanda yake bayan kasa su firgita, sashinsu ya gauraya da sashi saboda tsoron abin da zai biyo bayan busar, watau hisabi da sakamako, sai fa wadanda Allah ya ga dama ya toge su daga wannan firgicin domin nuna wata falalarsa gare su. Dukkan halittu a wannan rana za su zo wa Allah suna masu mika wuya, masu da'a gare shi.
Sannan a ranar mutum zai ga duwatsu ya yi zaton a tsaye suke cak ba sa motsi alhalin kuwa gudu suke shekawa kamar girgije a sama, saboda tsananin tsoro. Wannan aikin Allah kenan wanda ya kyauta halittar komai, shi ne wanda yake tafiyar da wadannan duwatsu kamar haka. Allah ya tabbatar da cewa lalle shi masanin abin da bayinsa suke aikatawa ne, kuma zai saka wa kowa gwargwadon aikinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da daukaka) ya bayyana yadda sakamakonsa yake na adalci da falala, da cewa duk wanda ya zo a ranar alkiyama da imani da aiki na kwarai, to yana da sakamakon Aljanna. Wannan falala ce ta Allah gare shi. Kuma masu irin wannan matsayi su amintattu ne daga firgitar wannan ranar.
Wanda kuwa ya zo da kafirci da sabon Allah to sakamakon wadannan wutar Jahannama ce. Za a rika yi musu tambaya irin ta wulakanci da kaskanci, da cewa shin za a saka musu da wani abu ne in ba da abin da suka kasance suna aikatawa ba na kafirci da sabon Allah?

Daga wadannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin kisa da farauta da zalunci a haramin Makka.

2. Bayanin ayyukan Manzon Allah (ﷺ) su ne bautar Allah da mika wuya gare shi da karanta Alkur'ani, domin ya zama gargadi da yankan hanzari da koyarwa da kuma neman kusanci da Allah.

3. Wajabcin gode wa Allah a bisa ni'imominsa masu yawa.

4. Bayani a kan cewa kowa sakamakon aikinsa zai girba a ranar alkiyama; in alheri ne ya ga alheri, in kuma sharri ne to zai ga sharri.

5. Tabbatar mu'ujizar Alkur'ani domin Allah (Mai tsarki da daukaka) ya yi wa kafirai alkawarin sai ya nuna musu ayoyinsa masu nuna Kadaitakarsa da gaskiyar Manzonsa kuma hakan ya zo ya tabbata kamar yadda ya ambata.

Suratun Namli (91-93)

إِنَّمَآ أُمِرۡتُ أَنۡ أَعۡبُدَ رَبَّ هَٰذِهِ ٱلۡبَلۡدَةِ ٱلَّذِي حَرَّمَهَا وَلَهُۥ كُلُّ شَيۡءٖۖ وَأُمِرۡتُ أَنۡ أَكُونَ مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ٩١ وَأَنۡ أَتۡلُوَاْ ٱلۡقُرۡءَانَۖ فَمَنِ ٱهۡتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهۡتَدِي لِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن ضَلَّ فَقُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلۡمُنذِرِينَ ٩٢ وَقُلِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ سَيُرِيكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ فَتَعۡرِفُونَهَاۚ وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ٩٣

91. (Ka ce da su): “Ni dai an umarce ni ne kawai da in bauta wa Ubangijin wannan garin (Makka) wanda Ya mayar da shi mai alfarma, kuma komai nasa ne; kuma an umarce ni da in zama cikin Musulmi.

92. “An kuma (umarce ni) da in karanta Alƙur’ani; don haka duk wanda ya shiriya, to ya shiriya ne don amfanin kansa; wanda kuwa ya ɓace sai ka ce (da shi): ‘Da ma ni ina cikin masu gargaɗi ne kawai’”.

93. Ka kuma ce: “Dukkan yabo ya tabbata ga Allah; ba da daɗewa ba zai nuna muku ayoyinsa, za kuma ku san su. Ubangijinka kuma ba rafkananne ba ne game da abin da kuke aikatawa.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya faɗa wa mushirikai cewa shi fa an umarce shi ne ya bauta wa Ubangijin wannan gari na Makka wanda ya mayar da shi mai alfarma, don haka ya haramta zubar da jini a cikinsa, ko a zalunci wani ko a kashe dabbar farauta a cikinsa ko a sare bishiyarsa. Mulkin komai nasa ne. Ya kuma umarci Manzonsa ya zama cikin Musulmi masu miƙa wuya ga Allah da yi masa biyayya.
Sannan ya faɗa musu cewa ya umarce shi ya karanta wa mutane Alƙur’ani, duk wanda ya karɓi shiriyarsa ya yi aiki da karantarwarsa to don amfanin kansa ne, wanda kuwa ya ɓace ya bijire wa karantarwarsa ya ƙi aiki da shi ko ma ya ƙaryata shi, to ya sanar da su cewa shi da ma yana cikin masu yi wa mutane gargaɗin azabar Allah ne kawai, amma shiriyarsu ba a hannunsa take ba.
Sai kuma a ayar ƙarshe ta wannan Sura Allah ya umarce shi da ya nuna godiyarsa da kirarinsa ga Allah bisa ga ɗimbin ni’imominsa da ba za su lissafu ba; ya tabbatar masa cewa zai nuna musu ayoyinsa a karan kansu da kuma ayoyin da suke sama da na ƙasa da ma waɗanda suke tattare da abin da ya arzuta su da shi, duk su gane su, su san su sanin da zai yi musu jagora zuwa ga sallama wa gaskiya, domin wanda zai shiryu ya shiryu a kan hujja, wanda kuma zai ɓace ya ɓace bayan hujja ta tsayu a kansa. Allah ya tabbatar da cewa shi ba rafkananne ba ne daga abin da mutane suke aikatawa, yana sane da komai kuma zai saka wa kowa a kan aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman sha’anin Alƙur’ani da mu’ujizarsa.

2. Babu masu amfanuwa da ayoyin Allah da labarin abubuwan da ya yi wa al’ummun farko waɗanda suka ƙaryata annabawa sai mutane masu imani. Gwargwadon imanin bawa gwargwadon yadda zai amfana da ƙissoshin da Allah yake bayarwa a cikin littafinsa.

3. Idan Allah ya nufi faruwar wani lamari, to sai ya hore sababbansa ya kuma zo da su ɗaya bayan ɗaya.

4. Duk yadda al’umma ta kai ga rauni bai dace ta yi rauni wajen neman haƙƙinta ba, kada kuma ta sami karayar zuci wajen yunƙurin fita daga ƙaskanci da samun ɗaukaka, musamman idan su ne ake zalunta.

5. Yana daga cikin makircin azzalumai masu mulki ƙoƙarin rarraba kan al’umma da rura wutar bambance-bambance na ƙabilanci da yare a tsakaninsu domin da haka ne za su ci gaba da yi musu mulkin kama-karya da zalunci da yaƙar masu fafutukar kawo gyara da sauyi.

6. Duk wani azzalumin mai mulki ba zai iya yin zaluncinsa ba sai ya sami taimakon wasu da kuma waɗanda za su kare muradinsa da ƙarfinsu da makamansu.

7. Duk wani zalunci a bayan ƙasa ƙarshensa shi ne rushewa da gushewa.

28-Suratul Kasas

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran wannan Sura da '*Suratul Kasas*' saboda kalmar '*Al-ƙasas*' da ta zo a aya ta 25. Kalmar tana nufin 'ba da labari'. Watau lokacin da Annabi Musa ya ba wa dattijon nan nagari da ke garin Madyana labarin abin da ya faru gare shi a ƙasar Masar kafin fitowarsa daga can.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya*, watau an saukar da ita lokacin Annabi (ﷺ) yana Makka bai yi hijira zuwa Madina ba.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba'in da tara (49) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *Suratun Naml* gabanin *Suratul Isra'i*.

4. Adadin ayoyinta:
Masana lissafin ayoyi sun haɗu a kan cewa ayoyin wannan Sura tamanin da takwas ne (88).

5. Babban Jigonta:
Tabbatar da cewa dukkan ƙarfi na Allah ne. Wanda Allah yake tare da shi kuma babu mai iya rinjayar sa ko da duk duniya za ta haɗu a kansa. Wanda Allah ya bar shi kuwa to ƙarfinsa ko dukiyarsa ba za su amfane shi da komai ba.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin darajar Alƙur'ani da nuni a kan cewa duk wani mai ji da fasaha da azancin magana cikin mushirikai sun gaza kawo kamarsa.
• Bayanin yadda Annabi Musa ya taso gidan Fir'auna har ya girma, da kuma dalilin rushewar mulkin Fir'auna.
• Tabbatar da ingancin manzancin Annabi (ﷺ) saboda yadda aka ji labaran mutanen da suka wuce a bakinsa duk da kasancewarsa ba ya rubutu ba ya karatu. Wannan ya tabbatar da cewa ana yi masa wahayi ne daga Allah.
• Matsanancin gargaɗi ga kafirai.
• Rushe ƙalubalantar da mushirikai suke yi wa Manzon Allah cewa ya nuna musu mu'ujiza irin ta Annabi Musa, kamar juya sanda ta zama macijiya.
• Gargaɗin su da tsoratar da su game da irin abin da ya sami al'ummun da suka ƙaryata manzanni a baya.
• Tunatar da su ni'imomin Allah da nuna musu dalilan da suke tabbatar da Kaɗaitakar Allah.
• Surar ta rufe ne da lallashin Manzon Allah (ﷺ) da yi masa albishir cewa Allah zai ɗora shi a kan kafirai maƙiyansa zai kuma damƙa ikon garin Makka a hannunsa.

Suratul Kasas (1-6)

طسٓمٓ ۝١ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ۝٢ نَتۡلُواْ عَلَيۡكَ مِن نَّبَإِ مُوسَىٰ وَفِرۡعَوۡنَ بِٱلۡحَقِّ لِقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ۝٣ إِنَّ فِرۡعَوۡنَ عَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَجَعَلَ أَهۡلَهَا شِيَعٗا يَسۡتَضۡعِفُ طَآئِفَةٗ مِّنۡهُمۡ يُذَبِّحُ أَبۡنَآءَهُمۡ وَيَسۡتَحۡيِۦ نِسَآءَهُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ مِنَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ۝٤ وَنُرِيدُ أَن نَّمُنَّ عَلَى ٱلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَنَجۡعَلَهُمۡ أَئِمَّةٗ وَنَجۡعَلَهُمُ ٱلۡوَٰرِثِينَ ۝٥ وَنُمَكِّنَ لَهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَنُرِيَ فِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَ وَجُنُودَهُمَا مِنۡهُم مَّا كَانُواْ يَحۡذَرُونَ ۝٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ƊA SIN MIM.

2. Waɗannan ayoyi ne na Littafi mabayyani.

3. Muna karanta maka labarin Musa da Fir’auna da gaskiya don mutane da suke yin imani.

4. Lalle Fir’auna ya yi ɗagawa a cikin ƙasar (Masar) ya kuma mayar da mutanenta ƙungiyoyi daban-daban, yana bautar da wata ƙungiyar daga cikinsu, yana yanka ‘ya’yayensu maza, yana kuma ƙyale matansu da rai. Lalle shi ya kasance cikin maɓarnata.

5. Muna kuma nufin za Mu yi baiwa ga waɗanda aka wulaƙanta a cikin ƙasar (Masar) Mu kuma mayar da su shugabanni, kuma Mu mayar da su magadan (mulkin Fir’auna).

6. Mu kuma kafa su a ƙasar, kuma Mu nuna wa Fir’auna da Hamana da rundunoninsu gaba ɗayansu abin da suke jin tsoro game da su (Banu Isra’ila).

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da wasu haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori da suka gabace ta. Dubi farkon *Suratul Baƙara* don ganin bayani a kansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗannan ayoyi da za su zo cikin wannan Sura ayoyi ne na littafi mai bayanin duk wasu buƙatu da bayi suke buƙatar saninsu.
Allah ya tabbatar wa Manzonsa cewa shi ne yake karanta masa labarin Annabi Musa da Fir’auna bisa gaskiya domin mutanen da suka yi imani, saboda su ne kaɗai za su amfana da shi.
Allah ya fara da ba shi labarin Fir’auna wanda ya yi ɗagawa a ƙasar Masar ya yi wa mutanen cikinta mulkin kama-karya ya mayar da su ƙungiyoyi daban-daban yana nuna bambanci tsakaninsu, yana kuma bautar da wata ƙungiyar daga cikinsu su ne Banu Isra’ila, yana yanka ‘ya’yansu maza yana ƙyale matansu domin su riƙa yi masa bauta a gidajensa duk dai domin ya ƙaskantar da su ya wulaƙanta su. Allah ya bayyana cewa lalle Fir’auna ya tabbata cikin maɓarnatan mutane waɗanda ba su da wani alheri duniya da lahira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sanar da cewa a lokacin da Fir’auna yake waccan aika-aika a kan Banu Isra’ila shi kuma yana nufin ya yi baiwa ga su Banu Isra’ila waɗanda ake wulaƙantawa a ƙasar Masar, ta hanyar hallaka Fir’auna babban maƙiyinsu da kawar musu da yanayin ƙaskanci da suke rayuwa a cikinsa, ya kuma mayar da su shugabanni waɗanda za a riƙa koyi da su wajen gaskiya da ayyukan alheri, sannan ya gadar musu da ƙasar Sham mai albarka bayan hallaka Fir’auna, sannan kuma ya kafa su a bayan ƙasa ya ba su mulki. Shi kuma Fir’auna da babban Wazirinsa mai taimaka masa wajen zalunci da ɓarna a bayan ƙasa, watau Hamana, tare da rundunarsu masu taimaka musu a harkokin mulkinsu na zalunci Allah ya nuna musu abin da suke tsoron aukuwarsa na gushewar mulkinsu da rushewar masarautarsu a hannun yaron da za a haifa daga ƙabilar Banu Isra’ila.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tausayawar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga mahaifiyar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kwantar mata da hankali ta hanyar yi mata albishir da cewa zai dawo mata da ɗanta kuma zai mayar da shi manzonsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan ƙaddara bawansa ya sha wahala domin ya haɗa shi da farin ciki mai girma ko ya kare shi daga wani sharri da ya zarce wahalar da ya sha tsanani, kamar yadda ya ƙaddara mahaifiyar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ta shiga matsanancin baƙin ciki na rabuwa da ɗanta, domin wannan ya zamanto wata hanya ce da zai dawo mata da ɗanta ta sami nutsuwa a ranta, zuciyarta ta yi sanyi, farin cikinta ya ƙaru.

3. Tsoro na ɗabi'a ba ya hana cikar imani ko ya kawar da shi.

Suratul Kasas (7-9)

وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰٓ أُمِّ مُوسَىٰٓ أَنۡ أَرۡضِعِيهِۖ فَإِذَا خِفۡتِ عَلَيۡهِ فَأَلۡقِيهِ فِي ٱلۡيَمِّ وَلَا تَخَافِي وَلَا تَحۡزَنِيٓۖ إِنَّا رَآدُّوهُ إِلَيۡكِ وَجَاعِلُوهُ مِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٧ فَٱلۡتَقَطَهُۥٓ ءَالُ فِرۡعَوۡنَ لِيَكُونَ لَهُمۡ عَدُوّٗا وَحَزَنًاۗ إِنَّ فِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَ وَجُنُودَهُمَا كَانُواْ خَٰطِـِٔينَ ٨ وَقَالَتِ ٱمۡرَأَتُ فِرۡعَوۡنَ قُرَّتُ عَيۡنٖ لِّي وَلَكَۖ لَا تَقۡتُلُوهُ عَسَىٰٓ أَن يَنفَعَنَآ أَوۡ نَتَّخِذَهُۥ وَلَدٗا وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٩

7. Muka kuma yi wa mahaifiyar Musa wahayi da cewa: "Ki shayar da shi; to yayin da kika ji masa tsoro, sai ki jefa shi a cikin kogi, kada kuma ki ji tsoro, kuma kada ki yi baƙin ciki; lalle Mu Masu dawo miki da shi ne, kuma Masu sanya shi ne cikin manzanni."

8. Sai mutanen Fir'auna suka tsince shi domin (daga baya) ya zama abokin gaba da kuma baƙin ciki a gare su. Lalle Fir'auna da Hamana da rundunoninsu sun kasance masu laifi.

9. Matar Fir'auna kuma ta ce: "(Shi) farin ciki ne a gare ni har da kai; kada ku kashe shi, muna fatan ya amfane mu ko kuma mu ɗauke shi a matsayin ɗa," alhali kuwa su ba su san (abin da zai faru ba).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci yadda mulkin Fir'auna zai zama nan gaba da kuma yadda zai ɗaukaka sha'anin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa ya kafa su a bayan ƙasa. Allah ya ambaci yadda Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya taso a gidan Fir'auna ƙarƙashin kulawarsa har zuwa lokacin da ya aiko shi zuwa ga Fir'auna da rundunarsa.
Bayan mahaifiyar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ta haife shi sai Allah ya yi mata wahayi yayin da ta shiga jin tsoron abin da zai faru gare shi idan har Fir'auna da zabaniyawansa suka sami labarin haihuwarsa. Allah ya umarce ta da ta shayar da shi, amma idan har ta ji tsoron Fir'auna game da shi to ta sanya shi cikin akwati ta jefa shi ruwa, watau ƙoramar Nil, kar kuma ta ji tsoron nutsewarsa a cikin ruwa ko Fir'auna ya hallaka shi, kuma kada ta yi baƙin cikin rabuwa da shi. Allah ya yi mata alƙawarin zai dawo mata da shi domin ta ci gaba da shayar da shi. Hasali ma ya tabbatar mata da cewa zai sanya shi cikin manzanninsa waɗanda yake aikowa zuwa ga bayinsa. Wannan kuwa ita ce mafi girman bushara ga mahaifiyar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
To mahaifiyar Annabi Musa dai hankalinta bai kwanta ba, don haka ta aikata abin da aka umarce ta da shi, ta saka shi cikin akwati ta rufe ta jefa shi cikin ƙoramar Nil.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma da ikonsa ya sanya ruwa ya ja akwatin Annabi Musa har zuwa gaɓar da mutanen Fir'auna suke shaƙatawa, a nan ne suka tsince shi suka kai shi gidan Fir'auna domin daga baya ya zame musu babban maƙiyi kuma abin baƙin cikinsu wanda a ƙarshe zai jawo musu halaka shi da jama'arsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar da cewa Fir'auna da Wazirinsa da rundunoninsu masu taimaka musu sun kasance masu aikata babban laifi saboda kafircinsu da zaluncinsu da ɓarnarsu a bayan ƙasa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar cewa yayin da Fir'auna ya ga jariri, watau Annabi Musa a gabansa sai bai nutsu da shi ba, har ma ya yi yunƙurin hallaka shi kamar yadda ya saba kashe jarirai maza, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jefa ƙaunar Musa a zuciyar matar Fir'auna Asiya sai nan take ta roƙi Fir'auna da kada ya kashe shi, domin tana ganin zai zama abin farin ciki a gare su nan gaba ko kuma ya amfane su ko ma su ɗauke shi a matsayin ɗansu. Allah ya bayyana cewa duk suna wannan hasashe ne bisa rashin sanin abin da zai kasance a hannun wannan jariri na rushewar mulkin Fir'auna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin tausayin mahaifiya ga ɗanta.

2. Haƙuri da juriya a kan abin da Allah ya ƙaddara wa bawa marar daɗi yana ƙara imani a zuciya.

3. Daga cikin manyan ni'imomin Allah ga bawa shi ne ya nufe shi da haƙuri da juriya yayin da yake cikin tashin hankali; wannan shi ne zai sa ya sami damar yin tunani cikin nutsuwa; idan zai furta wata magana ne sai ya furta wadda ta dace; idan kuma wani aiki ne zai aikata a lokacin sai ya yi abin da ya kamata. Saɓanin wanda zai rikice ya kasa samun natsuwa, to wannan ba zai amfana da hankalinsa ko tunaninsa ba.

4. Ko da bawa ya yi imani da cewa duk abin da Allah ya ƙaddara sai ya faru, kuma alƙawarin Allah gaskiya ne sai ya auku, wannan ba zai hana shi riƙo da sabubba ba waɗanda aka umarce shi da ya yi riƙo da su, kuma hakan ba zai kore masa imaninsa ba ko gaskatawarsa da abin da Allah ya labarta. Mahaifiyar Annabi Musa duk da cewa Allah ya yi mata alƙawarin dawo mata da ɗanta hakan bai hana ta yin nata ƙoƙarin ba, don haka ne ta aika 'yar'uwarsa ta umarce ta da ta bi sawunsa.

5. Yana daga cikin rahamar Allah ga rarraunan bawansa idan ya nufi karrama shi sai ya nuna masa wata aya da za ta ƙara masa imaninsa, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dawo wa da mahaifiyar Annabi Musa ɗanta domin ta tabbatar da cewa alƙawarin Allah gaskiya ne.

Suratul Kasas (10-13)
وَأَصۡبَحَ فُؤَادُ أُمِّ مُوسَىٰ فَٰرِغًاۖ إِن كَادَتۡ لَتُبۡدِي بِهِۦ لَوۡلَآ أَن رَّبَطۡنَا عَلَىٰ قَلۡبِهَا لِتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٠ وَقَالَتۡ لِأُخۡتِهِۦ قُصِّيهِۖ فَبَصُرَتۡ بِهِۦ
عَن جُنُبٖ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ١١ ۞وَحَرَّمۡنَا عَلَيۡهِ ٱلۡمَرَاضِعَ مِن قَبۡلُ فَقَالَتۡ هَلۡ أَدُلُّكُمۡ عَلَىٰٓ أَهۡلِ بَيۡتٖ يَكۡفُلُونَهُۥ لَكُمۡ وَهُمۡ لَهُۥ نَٰصِحُونَ ١٢
فَرَدَدۡنَٰهُ إِلَىٰٓ أُمِّهِۦ كَيۡ تَقَرَّ عَيۡنُهَا وَلَا تَحۡزَنَ وَلِتَعۡلَمَ أَنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ١٣

10. Zuciyar mahaifiyar Musa kuma ta wayi gari ba komai a cikinta (sai tunaninsa); ba shakka sauran ƙiris ta bayyana shi, ba don Mun ɗaure zuciyarta ba don ta zama cikin muminai.

11. Ta kuma ce da 'yar'uwarsa: "Ki bi sawunsa"; sai ta hango shi daga nesa, su kuwa ba su gane ita ('yar'uwarsa ba ce).

12. Da ma kuma can Mun haramta masa (nonon) masu shayarwa, sai ('yar'uwar tasa) ta ce: "Yanzu ba na nuna muku mutanen wani gida da za su shayar muku da shi ba, su kuma za su kyautata masa?"

13. Sai Muka dawo da shi wurin mahaifiyarsa don hankalinta ya kwanta kuma don kada ta yi baƙin ciki, don kuma ta san cewa alƙawarin Allah gaskiya ne, sai dai kuma yawancinsu ba sa fahimtar (haka).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin da mahaifiyar Annabi Musa ta shiga bayan jin cewa ya faɗa hannun babban maƙiyinsa Fir'auna wanda a koyaushe daga wannan lokacin zai iya hallaka shi kamar yadda ya saba yi ga 'ya'yan Banu Isra'ila maza. Sai ta wayi gari zuciyarta fayau ba komai a cikinta na al'amarin duniya in ban da tunanin ɗanta Annabi Musa, har saura ƙiris ta fito ta bayyana cewa ɗanta ne fa saboda tsananin shaƙuwarta da shi, ba don an yi sa'a Allah ya danne mata zuciyarta ba ya sa mata dauriya da haƙuri don ta zama daga cikin bayinsa muminai masu dogara ga Allah, masu haƙuri a kan abin da ya hukunta.
Bayan mahaifiyar Annabi Musa ta jefa shi a cikin ƙoramar Nilu sai ta aika 'yar'uwarsa cewa ta bi sawunsa ba tare da ta yarda wani ya gane ita 'yar'uwarsa ce ba. Sai ta bi sawunsa ta yadda take hango shi daga nesa kamar babu ruwanta da shi, ta zo wucewa ne kawai, Fir'auna da mutanensa ba su san abin da take ciki ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cikin cikar Kudurarsa sai ya tsara wa Annabi Musa cewa ba zai karɓi nonon duk wata mai shayarwa ba da aka kawo masa don su shayar da shi a gidan Fir'auna. To lokacin da 'yar'uwarsa ta fuskanci yadda suka damu da sai sun samar masa mai shayarwa, sai ta tambaye su ko suna son ta nuna musu mutanen wani gida waɗanda za su shayar musu da shi su kula da shi sosai su kyautata masa?
Da man kuwa wannan ita ce babbar buƙatarsu saboda tsananin ƙaunar Annabi Musa da ta mamaye zukatansu. Nan take suka amsa mata, ita kuma ta nuna musu mutanen gidansu inda mahaifiyarsu take.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya dawo wa da mahaifiyar Annabi Musa ɗanta don ta yi farin cikin ganin sa a kusa da ita, ta kuma daina baƙin cikin rabuwa da shi, har ila yau kuma ta tabbatar da cewa alƙawarin da Allah ya yi mata na dawo mata da shi gaskiya ne babu wani kokwanto a cikinsa. Sai dai yawancin mutane ba su san da wannan alƙawarin ba sannan kuma ba su san cewa ita uwarsa ce ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin kashe kafiri ba tare da wani haƙƙi ba.

2. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) mutum ne ƙaƙƙarfan gaske.

3. Duk wani aiki da bawa zai yi wanda ya karkace daga dokar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) to aikin Shaiɗan ne.

4. Babbar manufar da annabawa suke ƙoƙarin kaiwa gare ta ita ce samun gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da dacewa da yardarsa.

5. Yana daga cikin ladubban addu'a bawa ya yi iƙirari da laifinsa a gaban Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Kasas (14-17)
وَلَمَّا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَٱسۡتَوَىٰٓ ءَاتَيۡنَٰهُ حُكۡمٗا وَعِلۡمٗاۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٤ وَدَخَلَ ٱلۡمَدِينَةَ عَلَىٰ حِينِ غَفۡلَةٖ مِّنۡ أَهۡلِهَا فَوَجَدَ فِيهَا رَجُلَيۡنِ يَقۡتَتِلَانِ هَٰذَا مِن شِيعَتِهِۦ وَهَٰذَا مِنۡ عَدُوِّهِۦۖ فَٱسۡتَغَٰثَهُ ٱلَّذِي مِن شِيعَتِهِۦ عَلَى ٱلَّذِي مِنۡ عَدُوِّهِۦ فَوَكَزَهُۥ مُوسَىٰ فَقَضَىٰ عَلَيۡهِۖ قَالَ هَٰذَا مِنۡ عَمَلِ ٱلشَّيۡطَٰنِۖ إِنَّهُۥ عَدُوّٞ مُّضِلّٞ مُّبِينٞ ١٥ قَالَ رَبِّ إِنِّي ظَلَمۡتُ نَفۡسِي فَٱغۡفِرۡ لِي فَغَفَرَ لَهُۥٓۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ١٦ قَالَ رَبِّ بِمَآ أَنۡعَمۡتَ عَلَيَّ فَلَنۡ أَكُونَ ظَهِيرٗا لِّلۡمُجۡرِمِينَ ١٧

14. Lokacin kuma da ya kai ganiyar ƙarfinsa ya kuma kammala, sai Muka ba shi hukunci da ilimi. Kamar haka kuwa Muke saka wa masu kyautatawa.

15. Sai ya shiga cikin birnin a lokacin hutawar mutanensa, sai ya sami mutum biyu a cikinsa suna faɗa; wannan ɗan ƙabilarsa ne, wannan kuma daga maƙiyansa, sai ɗan ƙabilar tasa ya nemi taimakonsa a kan wanda yake daga maƙiyansa; to sai Musa ya naushe shi, sai kuwa ya kashe shi; (da ya ga haka sai) ya ce: “Wannan yana daga aikin Shaiɗan, lalle shi kuwa maƙiyi ne mai ɓatarwa na fili.”

16. Ya ce: “Ya Ubangijina, lalle ni na zalunci kaina, sai Ka yi min gafara,” sai ko Ya yi masa gafara. Lalle Shi kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

17. Ya ce: “Ya Ubangijina, saboda ni’imar da Ka yi min, ba zan taɓa zama mai taimakon masu laifi ba.”

Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da rayuwa a gidan Fir’auna ƙarƙashin kulawar mahaifiyarsa da renonta, yana sanya tufafi irin na mutanen gidan Fir’auna, yana hawan abin hawa irin nasu, mahaifiyarsa kuwa hankalinta a kwance, domin tana tare da ɗanta a koyaushe, babu wata fargaba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana cewa yayin da Annabi Musa ya kai shekarun cikar ƙarfinsa sai ya ba shi fahimta da ilimin sanin addinin Banu Isra’ila tun gabanin a ba shi annabta. Allah ya tabbatar da cewa kamar yadda ya yi wa Annabi Musa irin wannan kyakkyawan sakamako saboda kyautatawarsa to hakanan yake saka wa duk wasu masu kyautatawa a kowane zamani a kuma kowane wuri.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da cewa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga cikin birnin Masar a lokacin da mutane suke gidajensu suna hutawa, sai ya ci karo da wasu mutane su biyu suna faɗa da doke-doke, ɗayansu daga ƙabilarsa ne Banu Isra’ila, ɗayan kuwa daga ƙabilar Kibɗawa mutanen Fir’auna abokan gabar Annabi Musa da jama’arsa ne. Sai ɗan ƙabilar Annabi Musa ya nemi taimakonsa a kan Baƙibɗe maƙiyinsu, sai Annabi Musa ya naushe shi da hannunsa sai ko wannan naushin ya yi sanadin mutuwarsa, sai Annabi Musa ya yi nadama da faruwar wannan abu, ya ce lallai wannan aikin Shaiɗan ne, maƙiyi mai ɓatarwa, mai bayyana adawarsa a fili ga mutane.
Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙi Ubangijinsa yana mai iƙirari da laifinsa a gabansa cewa lallai shi ya zalunci kansa da ya kashe wannan Baƙibɗe, don haka yana roƙon Allah ya gafarta masa zunubinsa. Allah kuwa ya tabbatar mana cewa ya gafarta wa Annabi Musa, lallai kuma shi mai gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai jin ƙan su ne.
Sannan Annabi Musa ya sake tabbatar wa da Allah cewa saboda ni’imar da ya yi masa ya ba shi ƙarfi da ilimi da hikima, ya yi alƙawarin ba zai taɓa zama mai taimakon masu aikata laifi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawa sukan ji tsoro irin na ɗabi’a, wannan kuwa ba abu ne da zai rage matsayinsu a wurin Allah ba.
2. Taimakon farko da Annabi Musa ya ba wa Ba’isra’ile da kuma yunƙurin da ya yi na biyu domin taimakonsa ya nuna cewa lalle ba shi ne marar gaskiya ba, domin da shi ne marar gaskiya da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai yi niyyar taimaka masa ba.

3. Mutum ya ba wa wani labarin shirin cutar da shi da ake ba ya zama gulma; zai ma iya zama wajibi a kansa ya aikata hakan, kamar yadda mutumin da ya fito daga can ƙarshen gari ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

4. Idan mutum ya ji tsoron za a iya hallaka shi idan ya zauna a gari ko za a cutar da shi, to bai halatta ya zauna ya jefa kansa cikin hallaka ba.

Suratul Kasas (18-21)

فَأَصۡبَحَ فِي ٱلۡمَدِينَةِ خَآئِفٗا يَتَرَقَّبُ فَإِذَا ٱلَّذِي ٱسۡتَنصَرَهُۥ بِٱلۡأَمۡسِ يَسۡتَصۡرِخُهُۥۖ قَالَ لَهُۥ مُوسَىٰٓ إِنَّكَ لَغَوِيّٞ مُّبِينٞ ١٨ فَلَمَّآ أَنۡ أَرَادَ أَن يَبۡطِشَ بِٱلَّذِي هُوَ عَدُوّٞ لَّهُمَا قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ أَتُرِيدُ أَن تَقۡتُلَنِي كَمَا قَتَلۡتَ نَفۡسَۢا بِٱلۡأَمۡسِۖ إِن تُرِيدُ إِلَّآ أَن تَكُونَ جَبَّارٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا تُرِيدُ أَن تَكُونَ مِنَ ٱلۡمُصۡلِحِينَ ١٩ وَجَآءَ رَجُلٞ مِّنۡ أَقۡصَا ٱلۡمَدِينَةِ يَسۡعَىٰ قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّ ٱلۡمَلَأَ يَأۡتَمِرُونَ بِكَ لِيَقۡتُلُوكَ فَٱخۡرُجۡ إِنِّي لَكَ مِنَ ٱلنَّٰصِحِينَ ٢٠ فَخَرَجَ مِنۡهَا خَآئِفٗا يَتَرَقَّبُۖ قَالَ رَبِّ نَجِّنِي مِنَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢١

18. Sai ya wayi gari a cikin birnin a tsorace yana ɗar-ɗar, sai ga wanda ya nemi taimakon nan nasa a jiya yana sake neman taimakonsa, (sai) Musa ya ce da shi: “Lalle kai dai ɓatacce ne a fili!”

19. To lokacin da ya nufi wawurar abokin gabar tasu (sai mai neman taimakon) ya ce: “Ya Musa, shin yanzu nufi kake ka kashe ni kamar yadda ka kashe rai a jiya? Ba abin da kake nufi sai ka zama mai tsaurin rai a bayan ƙasa; ba ka kuma nufin ka zama cikin masu kawo gyara.”

20. Sai wani mutum (mumini daga mutanen Fir’auna) ya zo daga can ƙarshen birnin yana gaggawa, ya ce: “Ya Musa, lalle manyan gari (suna can) suna shawara a kanka don su kashe ka, to ka fita (daga birnin nan), lalle ni ina cikin masu yi maka nasiha.”

21. Sai ya fita daga cikinsa (wato birnin) a tsorace yana ta ɗar-ɗar, ya ce: “Ya Ubangijina, Ka tserar da ni daga azzaluman mutanen nan.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan abin da ya faru na kashe Baƙibɗe sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya wayi gari a cikin birnin Masar a tsorace yana zuba idon ya ga abin da zai biyo baya, sai kuma ga mutumin nan da ya nemi taimakonsa jiya a kan Baƙibɗe yau ma yana rigima da wani Baƙibɗen daban yana kuma neman taimakonsa, sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zarge shi da cewa lalle shi mutum ne ɓatacce matuƙa.
Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yunƙura zai rarumi wannan Baƙibɗe, sai Ba’isra’ilen ya zaci shi za a raruma, sai ya zargi Annabi Musa da cewa, yana son shi ma ya kashe shi ne kamar yadda ya kashe wani rai jiya? Ya ƙara da cewa lallai Annabi Musa yana nufin zama mutum mai tsaurin kai azzalumi a bayan ƙasa mai kashe mutane ba gaira ba dalili, kuma ba ya nufin ya zama mai kawo gyara a gari sai dai ya yi ɓarna.
Daga nan fa sai labarin abin da Annabi Musa ya aikata ya bazu ya cika gari har ya kai kunnen Fir’auna da jama’arsa, nan da nan suka fara tattaunawa a asirce a kan za su kashe Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) amma kuma sai Allah ya ƙaddara wani mutum daga can ƙarshen birni ya ji abin da suke ƙulla wa Annabi Musa ya yi gaggawa ya zo wurinsa ya zayyana masa bayanin shawarar da manyan gari suka yanke na kashe shi, don haka ya yi masa nasihar cewa lalle ya fita daga wannan gari na Masar domin ya tsira da ransa.
Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya karɓi wannan nasihar ya kuma fita a tsorace yana tunanin abin da zai faru da shi, ya ɗaga hannu ya roƙi Allah ya tserar da shi daga azzaluman mutane masu nufin cutar da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu laifi mutum ya yi hijira ya bar garinsa domin tsira da rayuwarsa da addininsa.

2. Tausaya wa mutane da kyautata musu ko da sanayya tsakani ko babu sanayya halayya ce ta annabawa.
3. Yana daga cikin kyautatawa shayar da dabbobi ruwa da taimaka wa gajiyayye da mai rauni.

4. Ya dace mutum ya roƙi Allah ta hanyar bayanin halin da yake ciki duk kuwa da cewa Allah yana sane da abin da yake ciki, domin Allah yana son bawansa ya nuna ƙasƙantar da kai da tsananin buƙatuwa gare shi.

5. Kunya tana daga cikin kyawawan ɗabi'u, musamman ga 'ya'ya mata.

6. Kyakkyawar sakayya a kan wani aikin alheri da mutum ya yi daɗaɗɗiyar ɗabi'a ce a cikin mutanen kirki.

Suratul Kasas (22-25)

وَلَمَّا تَوَجَّهَ تِلۡقَآءَ مَدۡيَنَ قَالَ عَسَىٰ رَبِّيٓ أَن يَهۡدِيَنِي سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ٢٢ وَلَمَّا وَرَدَ مَآءَ مَدۡيَنَ وَجَدَ عَلَيۡهِ أُمَّةٗ مِّنَ ٱلنَّاسِ يَسۡقُونَ وَوَجَدَ مِن دُونِهِمُ ٱمۡرَأَتَيۡنِ تَذُودَانِۖ قَالَ مَا خَطۡبُكُمَاۖ قَالَتَا لَا نَسۡقِي حَتَّىٰ يُصۡدِرَ ٱلرِّعَآءُۖ وَأَبُونَا شَيۡخٞ كَبِيرٞ ٢٣ فَسَقَىٰ لَهُمَا ثُمَّ تَوَلَّىٰٓ إِلَى ٱلظِّلِّ فَقَالَ رَبِّ إِنِّي لِمَآ أَنزَلۡتَ إِلَيَّ مِنۡ خَيۡرٖ فَقِيرٞ ٢٤ فَجَآءَتۡهُ إِحۡدَىٰهُمَا تَمۡشِي عَلَى ٱسۡتِحۡيَآءٖ قَالَتۡ إِنَّ أَبِي يَدۡعُوكَ لِيَجۡزِيَكَ أَجۡرَ مَا سَقَيۡتَ لَنَاۚ فَلَمَّا جَآءَهُۥ وَقَصَّ عَلَيۡهِ ٱلۡقَصَصَ قَالَ لَا تَخَفۡۖ نَجَوۡتَ مِنَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٥

22. Yayin da kuma ya sa gaba ya nufi wajen (birnin) Madyana, sai ya ce: "Ina fatan Ubangijina Ya shiryar da ni hanyar da ta fi dacewa."

23. Lokacin da kuma ya iso mashayar ruwa ta Madyana sai ya sami wani gungun mutane suna shayar (da dabbobinsu), ya kuma sami wasu mata su biyu a gefensu suna kare (dabbobinsu); sai ya ce (da su): "Me ya same ku ne?" Sai suka ce: "Mu ai ba ma shayarwa har sai duk makiyaya sun watse, kuma mahaifinmu tsoho ne tukub."

24. To sai ya shayar musu (da dabbobin nasu), sannan ya koma wurin wata inuwa ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ni mabuƙacin duk wani alhairi ne da za ka hore mini!"

25. Sai ɗayarsu ta zo masa tana tafiya cikin jin kunya ta ce: "Babana yana kiran ka don ya saka maka ladan shayarwar da ka yi mana." To lokacin da ya zo wurinsa ya kuma ba shi labarin(sa) sai ya ce da shi: "Kada ka ji tsoro, ka tsira daga azzaluman mutane."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fita daga Masar ya kama hanyar Madyana sai ya roƙi Allah Ubangijinsa cewa ya shiryar da shi hanyar da ta fi dacewa domin samun kuɓuta daga azzalumai.
Allah ya ci gaba da cewa, lokacin da Annabi Musa ya isa garin Madyana ya nufi wata rijiya inda ya sami mutanen garin suna shayar da dabbobinsu, a gefe guda kuma sai ya hango wasu mata su biyu zaune suna tsare da dabbobinsu ba su gauraya da sauran mutane ba, sai ya matsa kusa ya tambaye su ko me ya sa ba su shiga tare da mutane su shayar da dabbobinsu ba? Sai suka amsa masa da cewa ai sun saba da man haka suke yi, ba sa shayar da dabbobinsu har sai kowa ya watse don gudun cakuɗuwa da maza. Sannan suka faɗi uzurin mahaifinsu da yake aiko su suna mata shi ba ya zuwa da kansa da cewa, mahaifinsu tsoho ne tukub ba zai iya aikin shayar da dabbobi ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Musa ya tausaya wa 'yan matan nan, ya shayar musu da dabbobinsu ba tare da ya nemi wani lada a wajensu ba, daga nan ya koma wata inuwa domin ya

huta saboda tsananin zafin rana da ake yi a lokacin. A nan ne ya roki Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya hore masa abincin da zai ci domin yana cikin matsananciyar buƙata.
To waɗannan ‘yan mata kuwa sai suka koma gida suka ba wa mahaifinsu labarin duk abin da ya faru tsakaninsu da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sai ya aika ɗaya daga cikinsu zuwa gare shi domin ta kirawo masa shi, sai ta zo masa tana tafiya cikin jin kunya ta gaya masa cewa mahaifinta yana kiran sa don ya biya shi ladan shayar musu da dabbobi da ya yi. Annabi Musa ya amsa wannan kira nasa ya kuma je ya ba shi labarinsa gaba ɗaya, sai wannan tsoho mutumin kirki ya kwantar wa da Annabi Musa hankali ya nuna masa kada ya ji wani tsoro, ya tabbatar masa cewa ya tsira daga azzaluman mutane, watau Fir’auna da rundunarsa domin ba su da wani iko da garin Madyana, don haka ba za su iya cutar da shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan mutum ya yi wani aiki don Allah amma sai aka yi masa wata sakayya a kai ba tare da ya nufi hakan a zuciyarsa ba, to babu laifi a gare shi.

2. Halaccin ɗaukar mutum aiki a biya shi lada a kansa.

3. Babu laifi mutum ya nema wa ‘yarsa mijin aure na gari.

4. Mafi alherin ma’aikaci shi ne ƙaƙƙarfa kuma mai amana.

5. Yana daga cikin kyawawan ɗabi’u mutum ya kyautata mu’amalarsa ga wanda yake yi masa aiki ko hadiminsa, kada kuma ya riƙa saka shi aikin da ya fi ƙarfinsa ko wanda zai ƙuntata masa.

6. Halaccin ƙulla yarjejeniya ta aiki ba tare da samun shaidu a kai ba.

7. Ya shahara a wurin masu tafsiri faɗar cewa wannan tsoho na gari shi ne Annabi Shu’aibu. Wannan magana ce mai rauni, saboda dalilai kamar haka:
a) Kasancewar Annabi Shu’aibu an aiko shi zuwa ga mutanen Madyana, sannan kuma Annabi Musa ya je Madyana wannan bai isa hujjar a ce sun haɗu ba, domin babu wani tabbataccen dalili a kan cewa Annabi Musa ya riski zamanin Annabi Shu’aibu ballantana ma har a ce sun haɗu da juna.
b) Kuma Allah ya bayyana cewa mutanen Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba su da nisa da mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su kuma mutanen Annabi Luɗu Allah ya hallaka su ne tun a zamanin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Kuma abu ne sananne a wurin masana tarihi cewa, akwai tazara mai nisa tsakanin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wadda ta ɗara shekara ɗari huɗu.
c) Hakanan shi Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah ya hallaka mutanensa bayan sun ƙaryata shi, babu wanda ya yi saura daga cikinsu sai waɗanda suka yi imani da shi. Don haka ba zai kamata ba ko kaɗan muminai su hana ‘ya’yan annabinsu shayar da dabbobinsu har sai su sun gama shayar da nasu, ko kuma wani mutum baƙo ya zo ya taimaka musu.
d) Da a ce wannan tsoho bawan Allah shi ne Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) to da Allah ya ambaci sunansa, kuma da waɗannan ‘ya’ya nasa ba su ɓoye wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sunansa ba.
e) Kuma sannan a wannan Sura Allah ya ba da labarin cewa ya aiko Annabi Musa ne bayan ya hallaka al'ummun farko, watau al'ummun nan huɗu da yakan kawo labarinsu a jere da juna a cikin surori daban-daban, kamar '*Suratul A'araf* ' da *'Suratu Hud* ' da '*Suratu Shu'ara* ', su ne mutanen Annabi Nuhu da Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Luɗu sai mutanen Madyana. Wannan kuwa yana nufin Annabi Musa bai yi zamani da Annabi Shu'aibu da aka aika shi zuwa Madyana ba.

f) A taƙaice dai babu wani ingantaccen dalili da ya nuna cewa wannan bawan Allah Annabi Shu’aibu ne (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). [Dubi Ibn Kasir, Juzu’i na 6, shafi na 228-229].

Suratul Kasas (26-28)

قَالَتۡ إِحۡدَىٰهُمَا يَٰٓأَبَتِ ٱسۡتَـٔۡجِرۡهُۖ إِنَّ خَيۡرَ مَنِ ٱسۡتَـٔۡجَرۡتَ ٱلۡقَوِيُّ ٱلۡأَمِينُ ٢٦ قَالَ إِنِّيٓ أُرِيدُ أَنۡ أُنكِحَكَ إِحۡدَى ٱبۡنَتَيَّ هَٰتَيۡنِ عَلَىٰٓ أَن تَأۡجُرَنِي ثَمَٰنِيَ حِجَجٖۖ فَإِنۡ أَتۡمَمۡتَ عَشۡرٗا فَمِنۡ عِندِكَۖ وَمَآ أُرِيدُ أَنۡ أَشُقَّ عَلَيۡكَۚ سَتَجِدُنِيٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٢٧ قَالَ ذَٰلِكَ بَيۡنِي وَبَيۡنَكَۖ أَيَّمَا ٱلۡأَجَلَيۡنِ قَضَيۡتُ فَلَا عُدۡوَٰنَ عَلَيَّۖ وَٱللَّهُ عَلَىٰ مَا نَقُولُ وَكِيلٞ ٢٨

26. Sai ɗayarsu ta ce: “Babana, ka ɗauke shi aiki mana; don kuwa lalle ba wanda ya fi dacewa ka ɗauka aiki sai ƙaƙƙarfa, amintacce.”

27. Sai ya ce da (Musa): “Ina so in aura maka ɗaya daga ‘ya’yayen nan nawa guda biyu, a kan ka yi min aiki na shekara takwas; to amma idan ka cika goma to wannan raɗin kanka ne; ba na kuwa nufin in ƙuntata maka. Za ka same ni kuwa in Allah Ya yarda daga cikin nagartattun mutane.”

28. (Musa) ya ce: “Wannan tsakanina da kai ne; kowanne ɗayan lokatan biyu na cika to kada a ƙware ni; Allah kuwa shaida ne game da abin da muke faɗa.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ɗaya daga ‘yan matan nan biyu ta roƙi mahaifinta da ya ɗauki Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) aiki don ya riƙa yi musu kiwon dabbobinsu, domin tana ganin lalle ya cancanci ya yi wannan aiki saboda shi mutum ne da ya haɗa ƙarfi na jiki da kuma amana. Da ƙarfinsa zai yi duk abin da aka buƙaci ya yi, sannan kuma da amanarsa zai tsare musu dukiyarsu ba zai ha’ince su ba.
Sai mahaifinta ya amince da wannan shawara da ‘yarsa ta ba shi, ya sanar da Annabi Musa cewa yana da niyyar zai aura masa ɗaya daga ‘ya’yan nasa, amma sadakinta shi ne ya yi masa kiwon dabbobinsa na tsawon shekara takwas, sai dai in ya ga dama bisa raɗin kansa ya cike shekarun suka kai goma to wannan zaɓinsa ne kuma kyautatawa ce daga wurinsa ba dole ba ne, kuma shi ba ya son ya ƙuntata masa. Sannan ya tabbatar masa da cewa lalle zai same shi daga cikin mutane nagari masu cika alƙawari idan sun ɗauka.
Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ba shi amsa da cewa wannan tsakaninsa ne da shi, ya kuma amince da sharaɗinsa, kuma duk ɗayan lokutan biyu da ya ga dama ya ɗauka, shekara takwas ko goma, to ya sauke nauyin da ke kansa, kada kuma a nemi ƙarin wani lokaci a wurinsa ko a ƙware shi. Shi ma ya tabbatar masa da cewa lalle Allah ne wakili a kan duk wata yarjejeniya da za su ƙulla a tsakaninsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cika alƙawari ɗabi’a ce ta annabawa da mutane masu imani.

2. Magidanci shi ne aka ɗora wa alhakin fita ya nemo wa iyalansa abin da suke buƙata, ba su ne za su fita ba sai idan akwai wata larurar da za ta sanya su buƙaci haka, to babu laifi don sun fita.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana da Annabi Musa da gaske ya kuma ji sautinsa.

4. Tsoro na ɗabi’a ba laifi ba ne, annabawa ma sukan ji irin wannan tsoro a wasu lokuta.

Suratul Kasas (29-32)

۞فَلَمَّا قَضَىٰ مُوسَى ٱلۡأَجَلَ وَسَارَ بِأَهۡلِهِۦٓ ءَانَسَ مِن جَانِبِ ٱلطُّورِ نَارٗاۖ قَالَ لِأَهۡلِهِ ٱمۡكُثُوٓاْ إِنِّيٓ ءَانَسۡتُ نَارٗا لَّعَلِّيٓ ءَاتِيكُم مِّنۡهَا بِخَبَرٍ أَوۡ جَذۡوَةٖ مِّنَ ٱلنَّارِ لَعَلَّكُمۡ تَصۡطَلُونَ٢٩ فَلَمَّآ أَتَىٰهَا نُودِيَ مِن شَٰطِيِٕ ٱلۡوَادِ ٱلۡأَيۡمَنِ فِي ٱلۡبُقۡعَةِ ٱلۡمُبَٰرَكَةِ مِنَ ٱلشَّجَرَةِ أَن يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّيٓ أَنَا ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ٣٠ وَأَنۡ أَلۡقِ عَصَاكَۚ فَلَمَّا رَءَاهَا تَهۡتَزُّ كَأَنَّهَا جَآنّٞ وَلَّىٰ مُدۡبِرٗا وَلَمۡ يُعَقِّبۡۚ يَٰمُوسَىٰٓ أَقۡبِلۡ وَلَا تَخَفۡۖ إِنَّكَ مِنَ ٱلۡأٓمِنِينَ٣١ ٱسۡلُكۡ يَدَكَ فِي جَيۡبِكَ تَخۡرُجۡ بَيۡضَآءَ مِنۡ غَيۡرِ سُوٓءٖ وَٱضۡمُمۡ إِلَيۡكَ جَنَاحَكَ مِنَ ٱلرَّهۡبِۖ فَذَٰنِكَ بُرۡهَٰنَانِ مِن رَّبِّكَ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَإِيْهِۦٓۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمٗا فَٰسِقِينَ٣٢

29. To yayin da Musa ya cika lokacinsa ya kuma tafi da iyalinsa, sai ya hango wuta daga gefen (dutsen) Ɗuri, ya ce: “Lalle na hango wuta, (zan je don) in zo muku da labari daga wurinta ko kuma (in samo muku) wani garwashi na wutar don ku ji ɗumi.”

30. To lokacin da ya zo wurinta sai aka yi kira daga gefen kwari na damarsa a wani wuri mai albarka na bishiya, cewa: “Ya Musa, lalle Ni ne Allah Ubangijin talikai!

31. “Kuma ka jefar da sandarka;” to lokacin da ya gan ta tana girgiza kamar maciji sai ya ba da baya a guje, bai ko waiwaya ba. (Aka ce da shi): “Ya Musa dawo, kada ka ji tsoro; lalle kai kana cikin amintattu.

32. “Ka sanya hannunka a cikin wuyan rigarka, zai fito fari fat ba tare da wata cuta ba, kuma ka haɗe hannunka da kwiɓinka saboda tsoron (farinta); to biyu ɗin nan hujjoji ne daga Ubangijinka zuwa ga Fir’auna da mutanensa. Lalle su sun kasance mutane ne fasiƙai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya cika lokacin da suka yi yarjejeniya a kansa da wannan tsoho mutumin kirki. Bisa ga kyakkyawan zato ga Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi masa aiki ne na shekara goma don kyautata masa. Daga baya Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tuna gida, don haka begen danginsa ya kama shi sai ya ɗauki iyalansa daga Madyana ya nufi komawa da su ƙasar Masar, domin a zatonsa cewa tsawon lokacin da ya ɗauka ba ya ƙasar zai sa su manta da duk wani abu da ya faru a baya. Yana tsakiyar tafiya ne a cikin sahara cikin wani dare mai sanyi sai ya hango wuta a kusa da dutsen Ɗuri. Sai ya umarci iyalansa da su zauna nan inda suke domin ya tafi ya duba wannan wuta da ya hango, watakila ya samo musu labarin hanyar da za ta kai su Masar ko kuma ya zo musu da garwashin wuta wanda za su ɗumama jikinsu saboda sanyi.
To lokacin da Annabi Musa ya iso wajen wannan wuta sai Ubangijinsa (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo shi daga gefen kwari na dama a wannan wuri mai bishiya da Allah ya yi wa albarka da magana da shi, ya kuma kirawo shi da sunansa Musa, ya kuma tabbatar masa cewa shi ne Allah Ubangijin halittu. A nan ne ya umarce shi da ya jefar da sandar da take a hannunsa, nan take ya bi umarnin Allah ya jefar da ita ƙasa, sai kawai ya ga ta rikiɗe ta zama macijiya tana motsi tana gudu da sauri. Ganin haka sai ya tsorata ya juya baya da gudu bai dawo ba har sai da Ubangijinsa ya kirawo shi da cewa ya dawo kada kuma ya ji wani tsoro, domin lalle yana cikin amintattu waɗanda Allah yake ba su kariya.
Sannan kuma Allah ya umarce shi da ya shigar da hannunsa a cikin wuyan rigarsa zai ga hannun ya fito fari fat ba tare da wata cuta ba kamar albaras. Nan take kuwa sai ya sanya hannunsa a cikin wuyan rigarsa, da ya fito da shi sai ya gan shi fari sol kamar ƙanƙara.
Daga nan sai Allah ya umarce shi da ya haɗa hannunsa da gefen jikinsa domin ya daina jin tsoro da faɗuwar gaba. Allah ya tabbatar masa cewa waɗannan abubuwa biyu da ya ba shi, watau rikiɗewar sanda ta zama macijiya da kuma hannu mai haske kamar fitila, wasu hujjoji ne guda biyu daga Ubangijinsa da zai tafi da su wajen Fir’auna da jama’arsa, ya tabbatar masa cewa lalle Fir’auna da manyan fadawansa sun tabbata mutane ne fasiƙai waɗanda suka kangare wa Allah ta hanyar kafirci da yawan saɓonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin fasahar harshe ga mai kira zuwa ga Allah.

2. Mai kira zuwa ga Allah yana buƙatar waɗanda za su taya shi wannan muhimmin aiki nasa.

3. Babu wani mutum da ya nema wa ɗan'uwansa wata alfarma kamar yadda Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nema wa ɗan'uwansa Haruna alfarma a wurin Allah har kuma aka ba shi annabta da manzanci.

4. Babban abin lura a wannan ɓangare na labarin Annabi Musa shi ne fahimtar cewa manzanci wata baiwa ce Allah yake yi wa wanda ya ga dama ya kuma zaɓa daga cikin bayinsa, kuma manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ) kamar manzancin Annabi Musa ne, ya zo masa ne ba zato ba tsammani. Shi dai Annabi Muhammadu (ﷺ) an kirawo shi ne lokacin da yana cikin kogon dutsen Hira, kamar yadda aka kirawo Annabi Musa a gefen dutsen Ɗuri. Shi ma kuma ya tsorata sosai kamar yadda Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tsorata. Kuma Allah ya kwantar masa da hankalinsa kamar yadda ya yi wa Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), kuma shi ma Allah zai isar masa a kan maƙiyansa kamar yadda ya isar wa Annabi Musa nasa maƙiyan.

Suratul Kasas (33-35)
قَالَ رَبِّ إِنِّي قَتَلْتُ مِنْهُمْ نَفْسًا فَأَخَافُ أَن يَقْتُلُونِ ﴿٣٣﴾ وَأَخِي هَٰرُونُ هُوَ أَفْصَحُ مِنِّي لِسَانًا فَأَرْسِلْهُ مَعِيَ رِدْءًا يُصَدِّقُنِي إِنِّي أَخَافُ أَن يُكَذِّبُونِ ﴿٣٤﴾ قَالَ سَنَشُدُّ عَضُدَكَ بِأَخِيكَ وَنَجْعَلُ لَكُمَا سُلْطَانًا فَلَا يَصِلُونَ إِلَيْكُمَا بِآيَاتِنَا أَنتُمَا وَمَنِ اتَّبَعَكُمَا الْغَالِبُونَ ﴿٣٥﴾

33. (Musa) ya ce: "Ya Ubangijina, lalle ni na kashe musu wani mutum, to ina tsoron su kashe ni.

34. "Kuma ɗan'uwana Haruna shi ya fi ni fasahar harshe, sai Ka aike shi tare da ni ya zama mataimakina yana gaskata ni; lalle ni ina jin tsoron su ƙaryata ni."

35. (Sai Allah) Ya ce: "Za Mu ƙarfafa dantsenka da ɗan'uwanka kuma za Mu sanya muku wata hujja, don haka ba za su isa gare ku (da cuta) ba. Da ayoyinmu - ku da waɗanda suka bi ku - ku ne masu yin galaba."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya fahimci nauyin da Allah ya ɗora masa, sai kuma ya nemi wasu buƙatu daga Ubangijinsa. Da farko ya koka masa cewa a can baya fa ya taɓa kashe musu mutum, don haka yanzu yana tsoron idan ya je isar musu da saƙon Allah za su iya kashe shi.
Abu na biyu ya nemi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafe shi da ɗan'uwansa Haruna saboda ya fi shi fasahar harshe, don haka ya buƙaci ya aika su tare don ya riƙa gaskata maganarsa idan Fir'auna da mutanensa sun ƙaryata shi. Ya kuma nanata tsoronsa na cewa Fir'auna da mutanensa za su ƙaryata shi, domin wannan ita ce al'adar al'ummun da Allah ya aika wa annabawa a gabaninsa, watau ƙaryata manzanninsu.
Sai ko Allah ya amsa masa roƙonsa, ya tabbatar masa da cewa zai ƙara masa ƙarfi ta hanyar haɗa ɗan'uwansa tare da shi, kuma zai ba su wata hujja mai ƙarfi, don haka Fir'auna da fadawansa ba za su iya

isa gare su ba balle su cutar da su. Sannan a dalilin waɗannan ayoyi da Allah ya aiko su da su, su ne da mabiyansu za su yi rinjaye su sami nasara a kan maƙiyansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk ƙarfin hujja da bayyanarta maƙiya gaskiya sai sun soke ta da wata magana marar kan gado.

2. Fir’auna ya yi ƙoƙarin ya tabbatar wa mutanensa cewa shi ne abin bauta ba Allah ba, to amma sai ya kafa musu hujja da rashin sani, watau ya kore wa kansa ilimi. Wannan kaɗai ya isa ya tabbatar da cewa shi ne tantagaryar maƙaryaci, domin abin bauta na gaskiya dole ya kasance yana da cikakken ilimi babu abin da zai jahilta.

3. Tsananin kafircin Fir’auna da ya ƙaryata Annabi Musa har ya yi da’awar shi ne abin bauta, wai sam babu Allah, har ma ya riƙa barazanar cewa zai gina dogon gini don ya hau ya hango Ubangijin Annabi Musa.

Suratul Kasas (36-38)
فَلَمَّا جَآءَهُم مُّوسَىٰ بِاٰيَٰتِنَا بَيِّنَٰتٍ قَالُواْ مَا هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ مُّفۡتَرٗى وَمَا سَمِعۡنَا بِهَٰذَا فِيٓ ءَابَآئِنَا ٱلۡأَوَّلِينَ ٣٦ وَقَالَ مُوسَىٰ رَبِّيٓ أَعۡلَمُ بِمَن جَآءَ بِٱلۡهُدَىٰ مِنۡ عِندِهِۦ وَمَن تَكُونُ لَهُۥ عَٰقِبَةُ ٱلدَّارِۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٣٧ وَقَالَ فِرۡعَوۡنُ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمَلَأُ مَا عَلِمۡتُ لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرِي فَأَوۡقِدۡ لِي يَٰهَٰمَٰنُ عَلَى ٱلطِّينِ فَٱجۡعَل لِّي صَرۡحٗا لَّعَلِّيٓ أَطَّلِعُ إِلَىٰٓ إِلَٰهِ مُوسَىٰ وَإِنِّي لَأَظُنُّهُۥ مِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٣٨

36. To lokacin da Musa ya zo musu da ayoyinmu mabayyana sai suka ce: “Ai wannan ba wani abu ba ne face ƙagaggen sihiri, mu kuma ba mu taɓa jin wannan ba a wurin iyayenmu na farko.”

37. Musa kuma ya ce: “Ubangijina (Shi ne) Ya fi sanin wanda ya zo da shiriya daga wurinsa, da kuma wanda kyakkyawan ƙarshe zai kasance a gare shi; lalle yadda al'amarin yake, azzalumai ba sa rabauta.”

38. Fir’auna kuma ya ce: “Ya ku manyan gari, ban san kuna da wani abin bauta ba in ba ni ba, kai ko Hamana, shirya min ƙonannen taɓo sannan ka yi min dogon gini don in hango abin bautar Musa, lalle ni ina tsammanin cewa shi yana cikin maƙaryata.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da Annabi Musa ya zo wa Fir’auna da mutanensa tare da hujjoji bayyanannu sai suka ƙaryata shi suka zarge shi da cewa abin da ya zo da shi wani sihiri ne da shi ya ƙirƙira da kansa, kuma ma su ba su taɓa jin irin wannan maganar ta Annabi Musa a wurin iyayensu na farko ba, watau su dai ba su taɓa jin an ce abin bauta ɗaya ne ba tunda suke, don haka Annabi Musa ƙarya kawai yake shara musu.
Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya mayar musu da martani inda ya tabbatar musu da cewa Allah Ubangijinsa shi ne ya fi sanin wanda ya zo da shiriya daga wurinsa, ya kuma fi sanin wanda zai yi kyakkyawan ƙarshe a lahira, amma ko shakka babu su azzaluman mutane ba za su taɓa rabauta ba ta samun biyan buƙatarsu kuma su kuɓuta daga abin da suke tsoro.
To amma maimakon waɗannan maganganu na hankali da Fir’auna ya ji daga Annabi Musa su sanya jikinsa ya yi sanyi, sai girman kansa da rashin kunyarsa ga mahaliccinsa suka ƙaru, ya kira manyan fadawansa ya ƙara jaddada musu cewa shi fa bai san suna da wani abin bauta ba wanda ba shi ba. Sannan ya kirawo babban wazirinsa Hamana ya umarce shi da ya shirya ƙanannun tubala masu ƙarfi domin ya gina masa doguwar hasumiya da zai hau kanta wataƙila ya samu hango abin bautar Annabi Musa. Daga ƙarshe ma ya

nuna cewa shi a zatonsa Annabi Musa maƙaryaci ne kawai yake da'awar cewa Allah ne ya aiko shi zuwa gare su shi da mutanensa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman kai yana daga cikin manyan dalilai na rashin karɓar gaskiya da kuma wulaƙanta bayin Allah.

2. Mummunan ƙarshe ne sakamakon masu girman kai da bijire wa ayoyin Allah.

3. Yana daga cikin mummunar uƙubar Allah ga bawa ya sanya shi ya zamo jagora a cikin aikin sharri da ɓarna, kamar yadda ya zamanto babbar ni'ima ga bawa ya sanya shi ya zama abin koyi wurin aikata alheri da umarni da shi.

4. Karya tana da shugabanni da jagorori kamar yadda gaskiya take da nata shugabannin da jagororin.

Suratul Kasas (39-42)
وَٱسۡتَكۡبَرَ هُوَ وَجُنُودُهُۥ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَظَنُّوٓاْ أَنَّهُمۡ إِلَيۡنَا لَا يُرۡجَعُونَ ٣٩ فَأَخَذۡنَٰهُ وَجُنُودَهُۥ فَنَبَذۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡيَمِّۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٠ وَجَعَلۡنَٰهُمۡ أَئِمَّةٗ يَدۡعُونَ إِلَى ٱلنَّارِۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ لَا يُنصَرُونَ ٤١ وَأَتۡبَعۡنَٰهُمۡ فِي هَٰذِهِ ٱلدُّنۡيَا لَعۡنَةٗۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ هُم مِّنَ ٱلۡمَقۡبُوحِينَ ٤٢

39. Ya kuma yi girman kai shi da rundunoninsa a ƙasar (Masar) ba da gaskiya ba, suka kuma yi tsammanin cewa su ba za a komar da su zuwa gare Mu ba.

40. Sai Muka kama shi da rundunoninsa, sannan Muka watsa su a cikin kogi; to ka duba ka ga yadda ƙarshen azzalumai ya kasance.

41. Muka kuma mayar da su shugabanni masu kira zuwa ga wuta; ranar alƙiyama kuma ba za a taimake su ba.

42. Muka kuma bi su da la'anta a wannan duniyar; ranar alƙiyama kuma suna cikin waɗanda za a jefa cikin mummunan hali.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa girman kan Fir'auna da rundunarsa ya ƙara tsananta a ƙasar Masar ba tare da wata hujja ta gaskiya ba, suka kuma musanta tashi bayan mutuwa, suka yi tsammani cewa babu ranar alƙiyama ballantana a yi musu hisabi ko uƙuba a kan aika-aikar da suke yi a nan duniya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya damƙi Fir'auna da rundunoninsa ya watsa su a cikin kogi gaba ɗayansu suka hallaka. Daga nan ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya duba ya ga yadda ƙarshen azzalumai ya kasance, domin a fahimci cewa wannan ita ce sunnar Allah ga duk wanda yake ƙaryata manzanninsa da ayoyinsa.
Allah kuma ya bayyana cewa ya ƙaddara Fir'auna shi da manyan mataimakansa su kasance jagorori ababen koyi ga sauran ɓatattu da azzalumai, masu kiran mutane zuwa ga wuta ta hanyar abin da suke yaɗawa na kafirci da saɓon Allah a bayan ƙasa. Sannan kuma idan sun je lahira ba su da masu taimakon su don su kuɓutar da su daga azabar Allah, sai dai ma a ƙara ninninka musu mummunar azaba saboda munanan

ayyuka da aƙidu da suka shuka a bayan ƙasa suka kuma riƙa jan mutane cikinsu. To a kan haka za a rubuta musu mummunan sakamakonsu da kuma sakamakon waɗanda suka yi koyi da su wajen aiki irin nasu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya bi su da la'anta da wulaƙanci tun a nan duniya, a ranar alƙiyama kuma suna daga cikin waɗanda za su fuskanci mummunan hali da nesantawa daga rahamar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daga kan mutanen Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah bai sake hallaka wata al'umma hallakawa ta gaba ɗaya da wata azaba daga sama ba.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwatanta aiko Manzon Allah (ﷺ) zuwa ga wannan al'umma da aiko Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga Fir'auna da mutanensa, domin dukkansu ya aiko su ne bayan dogon lokaci da aka ɗauka ba a aiko da wani manzo ba.

3. Annabi Muhammadu (ﷺ) bai san gaibu ba. Jin labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga bakinsa babbar shaida ce a kan cewa ana yi masa wahayi ne daga Allah, hakan kuma yana tabbatar da gaskiyar manzancinsa, domin abu ne tabbatacce a wurin duk Larabawa maƙiyansa da masoyansa cewa, bai halarci wurin da aka yi magana da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba kuma shi tun da ba karatu yake yi ba balle a ce ya karanto ne, sai ya zama dole a amince da maganar wahayi da ya ce ana yi masa.

4. Aiko Manzon Allah (ﷺ) ya zo ne a lokacin tsananin buƙata gare shi.

Suratul Kasas (43-46)
وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ مِنۢ بَعۡدِ مَآ أَهۡلَكۡنَا ٱلۡقُرُونَ ٱلۡأُولَىٰ بَصَآئِرَ لِلنَّاسِ وَهُدٗى وَرَحۡمَةٗ لَّعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ٤٣ وَمَا كُنتَ بِجَانِبِ ٱلۡغَرۡبِيِّ إِذۡ قَضَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَى ٱلۡأَمۡرَ وَمَا كُنتَ مِنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ٤٤ وَلَٰكِنَّآ أَنشَأۡنَا قُرُونٗا فَتَطَاوَلَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡعُمُرُۚ وَمَا كُنتَ ثَاوِيٗا فِيٓ أَهۡلِ مَدۡيَنَ تَتۡلُواْ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِنَا وَلَٰكِنَّا كُنَّا مُرۡسِلِينَ ٤٥ وَمَا كُنتَ بِجَانِبِ ٱلطُّورِ إِذۡ نَادَيۡنَا وَلَٰكِن رَّحۡمَةٗ مِّن رَّبِّكَ لِتُنذِرَ قَوۡمٗا مَّآ أَتَىٰهُم مِّن نَّذِيرٖ مِّن قَبۡلِكَ لَعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ٤٦

43. Haƙiƙa kuma Mun bai wa Musa littafin (Attaura) bayan Mun hallaka al'ummu na farko don izina ga mutane da shiriya da rahama ko sa wa'azantu.

44. Kai kuma ba ka kasance a gefen (dutsen Ɗuri) na yamma ba lokacin da Muka yo wahayin manzanci zuwa ga Musa, ba ka kuma kasance cikin mahalarta wurin ba.

45. Sai dai cewa Mu Mun halicci al'ummu, sai nisan zamani ya tsawaita a gare su. Kuma ba ka kasance a zaune cikin mutanen Madyana ba kana karanta musu ayoyinmu, sai dai kuma Mu Mun kasance Masu aiko da (manzanni).

46. Kuma ba ka kasance a gefen (dutsen) Ɗuri ba, lokacin da Muka kirawo (Musa), sai dai wata rahama daga Ubangijinka, don ka gargaɗi wasu mutane da mai gargaɗi bai zo musu ba gabaninka ko sa wa'azantu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimar da ta sa aka bai wa Annabi Musa littafin Attaura aka kuma aika shi zuwa ga Banu Isra'ila. Hikimar ita ce ya ba shi Attaura ne bayan ya aika manzanni daban-daban zuwa ga al'ummun da suka gabace shi amma suka ƙaryata su sai Allah ya hallaka

su. A cikin littafin Attaura an bayyana wa mutane duk abin da zai amfane su don su riƙe shi da abin da zai cutar da su don su guje shi, sannan kuma rahama ne wanda ya ƙunshi alherin duniya da lahira gare su, domin su wa'azantu su riƙa tuntuntuni game da ni'imomin Allah gare su su kuma gode masa su yi imani da shi.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah bai hallaka wasu mutane ko wata al'umma da wata azaba daga sama ba tun bayan da ya saukar da Attaura a bayan ƙasa in ban da mutanen alƙaryar da aka mayar da su birrai. Shin ba ka ga faɗar Allah ba da yake cewa: "Haƙiƙa Mun bai wa Musa littafin (Attaura) bayan Mun hallaka al'ummu na farko don ya zama izina ga mutane da shiriya da rahama don su wa'azantu?" [Al-Hakim, *Al-Mustadrak,* Juzu'i na 2, Shafi na 408].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Manzonsa cewa bai kasance a gefen dutsen Ɗuri da ke yamma da Annabi Musa ba lokacin da ya yi masa wahayin manzanci zuwa ga Fir'auna da manyan fadawansa; watau ba ya wurin ballantana har ya san wannan labarin ya kuma bayar da shi ga mutane, sai dai abin da duk yake faɗa musu wahayi ne Allah ya yi masa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa buƙata ce ta kama kan aiko da manzo domin Allah ya halicci al'ummu da yawa bayan Annabi Musa sai lokaci ya tsawaita a gare su har suka manta da alƙawuran da suka yi tsakaninsu da Allah; ilimi ya yi ƙaranci sosai; buƙatar aiko da wani manzo ta tsananta, don haka Allah ya aiko da Annabi Muhammad (ﷺ) ya saukar masa da wahayi. Allah kuma ya bayyana wa Manzonsa cewa bai kasance yana zaune a cikin mutanen Madyana yana karantar da su ayoyin Allah ba, sai dai ya aiko shi ne daga wurinsa ya kuma yi masa wahayin labarin Annabi Musa da zamansa a garin Madyana, shi kuma ya sanar da mutane wannan labari da aka yi masa wahayinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake jaddada wa Manzonsa (ﷺ) cewa bai kasance a gefen dutsen Ɗuri ba lokacin da Allah ya kirawo Annabi Musa ya yi masa wahayinsa a lokacin ballantana ya riƙa ba wa mutane labarin abin da ya faru, sai dai ya aiko shi don ya zama rahama daga gare shi zuwa ga mutane, ya kuma yi masa wahayin duk abubuwan da suka faru da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don ya gargaɗi wasu mutane waɗanda mai gargaɗi bai zo musu ba gabaninsa, watau Kuraishawa da kuma Larabawa domin su wa'azantu da abin da za su ji daga wajensa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Aiko da manzanni yanke hanzari ne ga mutane.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya azabtar da wani bawa har sai ya yi masa bayanin dokokinsa da farko.

3. Kalubale ga kafirai da su zo da wani littafi ko tsari wanda ya fi na Allah da ya aiko manzanninsa da shi.

4. Duk wani tsari ko hukunci da ɗan'adam zai shirya wa kansa ba zai taɓa zama kamar na Allah ba balle har ya fi shi.

5. Duk wanda bai bi Manzon Allah ba to son zuciyarsa kawai yake bi, don babu wani abu na uku daga gaskiya sai ɓata.

6. An saukar da Alƙur'ani kaɗan-kaɗan saboda hikimomin da suke cikin yin hakan, kamar faɗakarwa da jan hankali lokaci bayan lokaci.

Suratul Kasas (47-51)

وَلَوۡلَآ أَن تُصِيبَهُم مُّصِيبَةُۢ بِمَا قَدَّمَتۡ أَيۡدِيهِمۡ فَيَقُولُواْ رَبَّنَا لَوۡلَآ أَرۡسَلۡتَ إِلَيۡنَا رَسُولٗا فَنَتَّبِعَ ءَايَٰتِكَ وَنَكُونَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٤٧ فَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ مِنۡ عِندِنَا قَالُواْ لَوۡلَآ أُوتِيَ مِثۡلَ مَآ أُوتِيَ مُوسَىٰۚ أَوَ لَمۡ يَكۡفُرُواْ بِمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ مِن قَبۡلُۖ قَالُواْ سِحۡرَانِ تَظَٰهَرَا وَقَالُوٓاْ إِنَّا بِكُلّٖ كَٰفِرُونَ ٤٨ قُلۡ فَأۡتُواْ بِكِتَٰبٖ مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِ هُوَ أَهۡدَىٰ مِنۡهُمَآ أَتَّبِعۡهُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٤٩ فَإِن لَّمۡ يَسۡتَجِيبُواْ لَكَ فَٱعۡلَمۡ أَنَّمَا يَتَّبِعُونَ أَهۡوَآءَهُمۡۚ وَمَنۡ أَضَلُّ مِمَّنِ ٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ بِغَيۡرِ هُدٗى مِّنَ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥٠ ۞وَلَقَدۡ وَصَّلۡنَا لَهُمُ ٱلۡقَوۡلَ لَعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ٥١

47. Kuma ba don kada wata masifa ta same su ba saboda abin da suka aikata da kansu sai su rika cewa: “Ya Ubangijinmu, ina ma da Ka aiko mana da wani manzo, da sai mu bi ayoyinka mu kuma kasance cikin muminai?”

48. To lokacin da gaskiya ta zo musu daga wajenmu sai suka ce: “Ina ma da an ba shi irin abin da aka bai wa Musa?” Yanzu ashe tun da can ba su kafirce da abin da aka bai wa Musa ba; suka ce: “Su biyun sihiri ne (wato Alkur’ani da Attaura) da suke taimakon juna?” Suka kuma ce: “Lalle mu mun kafirce da su gaba ɗaya.”

49. Ka ce (da su): “To ku zo da wani littafi daga wajen Allah wanda ya fi su nuna hanyar shiriya (wato Alkur’ani da Attaura), zan bi shi idan kun kasance masu gaskiya.”

50. To idan ba su amsa maka ba, to ka sani cewa ba abin da suke bi sai soye-soyen zukatansu kawai. Ba kuwa wanda ya fi ɓacewa kamar wanda ya bi son zuciyarsa ba tare da wata shiriya daga Allah ba. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai.

51. Hakika kuma Mun saukar musu da Alkur’ani (guntu-guntu) don su wa’azantu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimar aiko Manzon Allah (ﷺ), watau don yanke hanzarin kafirai. Domin da a ce wata azaba ta sauka a kansu saboda kafircinsu da yawan saɓon Allah da suke yi, to da sai su ce me ya sa Allah bai aiko musu da wani manzo ba wanda zai gargaɗe su ya tsoratar da su azabar Allah? Ai da haka ya faru da sun bi ayoyin da ya zo musu da su sun yi aiki da su sun kuma kasance daga cikin muminai masu bin umarnin Ubangijinsu. To ba don wannan ba da ya gaggauto musu azaba ya hallaka su, to amma ya jinkirta musu har sai da ya aiko musu da manzo daga cikinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo wa Kuraishawa da saƙo daga Allah, sai suka tambayi Yahudawa game da shi, su kuma sai suka nuna musu hanyar da za su ƙalubalance shi da ita, watau su tambaye shi cewa ko shi an ba shi irin mu’ujizojin da aka ba wa Annabi Musa, kamar sandarsa mai rikiɗewa ta zama macijiya da hannunsa mai haske kamar fitila ba tare da wata cuta ba? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya mayar musu da martani da cewa, ashe a baya can ba sun kafirce wa Attaura da aka ba wa Annabi Musa ba? Kuma yayin da Annabi ya zo musu da Alkur’ani shi ma ai watsi suka yi da shi, har ma suka ce wai Attaura da Alkur’anin ai dukkansu sihiri ne masu taimaka wa juna, don haka su ba su yi Imani da ko ɗaya daga cikinsu ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya neme su da su kawo wani littafin daga Allah wanda ya fi Attaura da Alkur’ani nuna hanyar shiriya; idan kuwa har sun zo da shi to shi ma Manzon Allah (ﷺ) zai bi shi ya yi imani da shi, idan har su masu gaskiya ne a kan maganar da suke faɗa game da su, watau Attaura da Alkur’ani.
Sai kuma ya bayyana musu cewa idan har sun kasa amsa wannan ƙalubale da ya yi musu, watau sun gaza kawo wani littafi wanda ya fi Attaura da Alkur’ani shiriya, to ya tabbatar da cewa ba su da wani dalili na ƙaryata shi in ban da bin son zuciya kawai, kuma lalle su sani cewa babu ɓataccen mutum da ya kai ga mai bin son zuciyarsa ya bar shiriya ta Allah da ta zo masa. Lalle kuma Allah ba ya shiryar da mutane azzalumai waɗanda suka cuci kansu da kafirci da saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimar saukar da Alƙur'ani guntu-guntu har ya cika ya haɗu da juna, da cewa, ya yi musu haka ne don su wa'azantu da abin da yake cikinsa su yi imani da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar ma'abota littafi waɗanda suka yi imani da Annabi (ﷺ) da Alƙur'ani suka kuma miƙa wuya ga Allah.

2. Falalar wanda yake kawar da mummunan aiki da kyakkyawa, da kuma kyautata wa mutane da arziƙin da Allah ya ba shi.

3. Falalar haƙuri a kan biyayya ga Allah da juriya game da tsangwamar jahilai.

Suratul Kasas (52-55)

ٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلِهِۦ هُم بِهِۦ يُؤۡمِنُونَ ٥٢ وَإِذَا يُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِهِۦٓ إِنَّهُ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّنَآ إِنَّا كُنَّا مِن قَبۡلِهِۦ مُسۡلِمِينَ ٥٣ أُوْلَٰٓئِكَ يُؤۡتَوۡنَ أَجۡرَهُم مَّرَّتَيۡنِ بِمَا صَبَرُواْ وَيَدۡرَءُونَ بِٱلۡحَسَنَةِ ٱلسَّيِّئَةَ وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ٥٤ وَإِذَا سَمِعُواْ ٱللَّغۡوَ أَعۡرَضُواْ عَنۡهُ وَقَالُواْ لَنَآ أَعۡمَٰلُنَا وَلَكُمۡ أَعۡمَٰلُكُمۡ سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمۡ لَا نَبۡتَغِي ٱلۡجَٰهِلِينَ ٥٥

52. Waɗanda Muka bai wa littafi a gabaninsa (Alƙur'ani) (suka tsaya a kansa) su suna yin imani da shi (Alƙur'ani).

53. Idan kuma ana karanta musu (Alƙur'anin) sai su ce: "Mun yi imani da shi, lalle shi gaskiya ne daga Ubangijinmu, lalle mu mun kasance Musulmi tun gabaninsa."

54. Waɗannan (su ne) za a ba su ladansu ninki biyu saboda haƙurin da suka yi. Kuma suna kawar da mummunan aiki da kyakkyawa, suna kuma ciyarwa daga abin da Muka arzuta su (da shi).

55. Idan kuma suka ji maganar banza sai su kau da kai daga gare ta, sai kuma su ce: "(Sakamakon) ayyukanmu yana gare mu, ku kuma na ayyukanku yana gare ku, kun kuɓuta daga gare mu, ba ruwanmu da wawaye!"

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wasu daga ma'abota littafi, watau Yahudawa waɗanda suka ci gaba da riƙo da Attaura suna yin imani da gaskiya tun gabanin a saukar da Alƙur'ani; to su waɗannan suna yin imani da abin da suka gani a littafinsu na labarin Manzon Allah da Alƙur'ani da siffofinsa. Kuma idan ana karanta musu Alƙur'ani sai su nuna cewa su lalle sun yi imani da shi, kuma lalle shi gaskiya ne daga Ubangijinsa, kuma su tun da ma can sun kasance Musulmi ne, domin sun riga sun yi imani da duk abin da manzanni suka zo musu da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗannan masu irin wannan siffar zai ninka musu ladan aikinsu sau biyu, na farko saboda haƙurin da suka yi na tsayawa kyam a kan imaninsu da duk abin da ya zo musu a cikin littafinsu; na biyu kuma saboda imanin da suka yi da Annabi (ﷺ) da Alƙur'ani bayan an aiko shi da shi.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mutum uku ana ba su ladansu sau biyu: Mutum daga cikin ma'abota littafi wanda ya yi imani da annabinsa ya kuma yi imani da ni; da bawan da ya bayar da haƙƙin Allah ya kuma bayar da haƙƙin iyayen gidansa; da kuma mutumin da yake da baiwa sai ya yi mata kyakkyawar tarbiyya sannan ya 'yanta ta ya kuma aure ta." [Bukhari #97 da Muslim #154].

An karɓo daga Abu Umama Al-Bahili ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk wanda ya musulunta daga cikin ma’abota littattafai biyu (Attaura da Linjila), to yana da ladansa sau biyu, yana da abin da muke da shi na haƙƙoki, kuma abin da ya wajaba kanmu shi ma ya wajaba a kansa, kuma duk wanda ya musulunta daga cikin mushirikai, to yana da ladansa, yana da abin da muke da shi na haƙƙoki, kuma abin da ya wajaba a kanmu shi ma ya wajaba a kansa.” [Ahmad #22234].

Sai kuma ya nuna sifarsu da cewa suna kawar da laifuffukan da suka yi ta hanyar aikata kyawawan ayyuka, kuma suna ciyar da abin da Allah ya arzuta su da shi a wajen ayyukan alheri.
Sannan Allah ya ci gaba da faɗar kyawawan halayen waɗannan mutane da cewa, su ne waɗanda idan suka ji maganar banza sukan kau da kai daga gare ta ba za su tanka ba ko su rama; sukan faɗa wa masu irin wannan maganar cewa kowa ya je da halinsa; su ayyukansu da suka aikata a kansu ne za a saka musu, su ma a kan ayyukansu za a yi musu sakayya; babu wanda za a ba shi ladan wani ko a yi masa uƙuba saboda laifin wani. Suka kuma nuna musu cewa sun kuɓuta daga gare su; ba za su zage su ba ba za su cuce su ba, kuma su ba sa neman su yi abota da jahilai, domin yin haka zai cutar da su a rayuwarsu ta duniya da ta addini.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kimsa shiriya a zuciya aikin Allah ne shi kaɗai; shi ne yake shiryar da wanda ya zaba a cikin bayinsa ya nufe shi da yin imani.

2. Bin gaskiya da riƙo da ita shi ne kaɗai hanyar samun zaman lafiya, ba hanyar haifar da tsoro ba, kamar yadda mushirikai suka riƙa riyawa.

3. Kafiran Makka sun ƙi yin imani da Annabi (ﷺ) ne wai don ganin mutane daga ko’ina suna nuna masa gaba da ƙiyayya, don haka idan sun yi imani da shi to su ma sun jefa kansu cikin gaba da ƙiyayya ta mutane. Wannan magana tasu tana nuna mummunan zatonsu ne ga Allah da ganin cewa ba zai taimaki addininsa ba, ba kuma zai ɗaukaka kalmarsa ba; Allah mai iya ɗora wasu mutane mabiya addininsa a kan kafirai su yi ta gana musu azaba iri-iri. Sai ga shi kuwa Allah ya nuna musu ƙaryar zatonsu, ya bai wa Annabinsa da Musulmi nasara a kan ɗaukacin magabtansu.

4. Tarihi yana maimaita kansa ne a yau, watau kamar yadda Kuraishawa suka kawo uzurinsu na rashin karɓar Musulunci da cewa suna tsoron kada sauran ƙabilun Larabawa su kama su su bautar da su ko su kashe su, to hakanan ma shugabannin ƙasashen Musulmi a yau suke guje wa aiki da shari’ar Musulunci da dokokinta don tsoron mugun martani na ƙasashen yamma da kuma tsoron a jefe su da miyagun sunaye, kamar ‘ta’addanci’ ko ‘tsattsauran ra’ayin addini’.

Suratul Kasas (56-57)
إِنَّكَ لَا تَهۡدِي مَنۡ أَحۡبَبۡتَ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَهۡدِي مَن يَشَآءُۚ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِٱلۡمُهۡتَدِينَ ٥٦ وَقَالُوٓاْ إِن نَّتَّبِعِ ٱلۡهُدَىٰ مَعَكَ نُتَخَطَّفۡ مِنۡ أَرۡضِنَآۚ أَوَ لَمۡ نُمَكِّن لَّهُمۡ حَرَمًا ءَامِنٗا يُجۡبَىٰٓ إِلَيۡهِ ثَمَرَٰتُ كُلِّ شَيۡءٖ رِّزۡقٗا مِّن لَّدُنَّا وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٥٧

56. Lalle kai ba ka iya shiryar da wanda ka so, sai dai Allah ne Yana shiryar da wanda Ya ga dama. Shi kuma ne Ya san masu shiryuwa.

57. Suka kuma ce: “Idan har Muka bi shiriya tare da kai, to za a kame mu (ribatattu) daga ƙasarmu”. (Ka ce da su): “Yanzu ashe ba Mu ne Muka ba su ikon Harami amintacce ba da ake kawo kowanne irin (nau’i) na ‘ya’yan itace gare shi don arzutawa daga gare Mu?” Sai dai kuma yawancinsu ba sa sanin (haka).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Manzonsa cewa shi ba zai iya shiryar da wanda yake so ba ya sanya shi ya yi imani da Allah da abin da aka aiko shi da shi na gaskiya; Allah ne kaɗai yake iya shiryar da wanda ya ga dama, sai ya datar da shi ya karɓi shiriyarsa, kuma shi ne ya fi kowa sanin masu shiryuwa daga cikin bayinsa.

An karɓo daga Al-Musayyab ɗan Hazn Al-Makhzumi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da Abu Ɗalib ya zo mutuwa sai Manzon Allah (ﷺ) ya je wurinsa sai ya iske Abu Jahal ɗan Hisham da Abdullahi ɗan Abu Umayya ɗan Mughira a wurinsa, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ya kai Baffana, ka faɗi ‘*La ilaha illallahu*’, kalmar da zan yi maka shaida da ita a gaban Allah.” Sai Abu Jahal da Abdullahi ɗan Abu Umayya suka ce masa: “Yanzu kai za ka watsar da addinin Abdulmuɗɗalib kenan?” Annabi bai gushe ba yana ta bijirar masa da wannan kalma, su kuma suna ta maimaita masa waccan magana tasu, har dai daga ƙarshe ya ce shi yana nan a kan addinin Abdulmuɗɗalib, ya ƙi amincewa ya furta Kalmar Shahada. Sai Annabi (ﷺ) ya ce: “Lalle tabbas zan nema maka gafara matuƙar ba a hana ni ba.” Sai ayar ta 113 a *Suratut Tauba* ta sauka, da kuma wannan ayar ta 56. [Bukhari #1360 da Muslim #24].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana uzurin da mushirikan Makka suka riƙa ba wa Manzon Allah (ﷺ) a kan rashin yin imani da shi, da cewa in sun amince sun bi shiriya tare da shi sun yi imani da abin da ya zo musu da shi, to za a fincike su daga ƙasarsu Makka su zama ribatattun yaƙi a hannun maƙiyansu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa, ashe ba shi ne ya ba su iko da Harami amintacce ba, watau Makka wadda aka haramta zubar da jini da zalunci a cikinta fiye da ko’ina, suna kuma samun aminci a cikinta babu mai iya kawo musu hari, sannan kuma ana kawo musu kayan marmari iri-iri daga ko’ina don Allah ya arzuta su daga arziƙinsa, to amma yawancinsu ba su san girman ni’imar da Allah ya yi musu ba ballantana su gode masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haɗarin zarmewa cikin rayuwar duniya da mantawa da godiyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da bauta masa.

2. Yana daga cikin rahamar Allah ga bayinsa kasancewarsa ba ya hallaka su sai bayan ya aiko musu da gargaɗi ta hanyar manzanninsa.

3. Girman haɗarin zalunci da mummunan ƙarshen azzalumi.

Suratul Kasas (58-59)

وَكَمْ أَهْلَكْنَا مِن قَرْيَةٍۭ بَطِرَتْ مَعِيشَتَهَاۖ فَتِلْكَ مَسَٰكِنُهُمْ لَمْ تُسْكَن مِّنۢ بَعْدِهِمْ إِلَّا قَلِيلًاۖ وَكُنَّا نَحْنُ ٱلْوَٰرِثِينَ ﴿٥٨﴾ وَمَا كَانَ رَبُّكَ مُهْلِكَ ٱلْقُرَىٰ حَتَّىٰ يَبْعَثَ فِىٓ أُمِّهَا رَسُولًا يَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِنَاۚ وَمَا كُنَّا مُهْلِكِى ٱلْقُرَىٰٓ إِلَّا وَأَهْلُهَا ظَٰلِمُونَ ﴿٥٩﴾

58. Kuma al’umma nawa ce Muka hallakar wadda ta butulce wa rayuwarta? To ga gidajensu can ba a zaune su ba a bayansu sai kaɗan; Mu ne Muka kasance magadan.

59. Kuma Ubangijinka bai zamanto Mai hallakar da alƙaryu ba har sai Ya aiko da manzo a cikin manyan biranensu, yana karanta musu ayoyinmu. Kuma ba Mu kasance Masu hallaka alƙaryu ba sai idan mutanensu sun zama azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dangogin azaba da hallakarwar da suka sami al'ummun da suka ƙaryata annabawa da cewa ya hallakar da alƙaryu da dama saboda sun kafirce wa ni'imar da ya yi musu sun zarme cikin saɓon sa. Kuma Larabawa su ne shaida, domin suna ganin gidajensu bayan an hallakar da su babu kowa zaune a cikinsu sai wasu 'yan tsirarun mutane matafiya da sukan ya da zango su zauna na ɗan lokaci. Allah kuma ya tabbatar da cewa shi ne mai gadon waɗannan gidajen nasu kuma mai gadon sama da ƙasa da duk abin da yake cikinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzo (ﷺ) cewa ba zai taɓa hallakar da wata al'umma ba har sai ya aika mata da manzonsa, kamar yadda ya aiko da Manzo (ﷺ) zuwa ga uwar alƙaryu, watau Makka, ya yanke wa mutanenta duk wani hanzari da uzuri, amma suka bijire. Kuma ba zai taɓa hallakar da mutanen kowace alƙarya ba idan suna kan gaskiya suna bin tafarki madaidaci, sai dai idan sun kasance azzalumai masu aikata kafirci da saɓon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duniya da ƙyale-ƙyalenta ba a bakin komai suke ba a wurin Allah.2. Mai hankali shi ne wanda yake fifita ni'ima mai ɗorewa a kan ni'ima mai ƙarewa.

3. Abin da Allah ya yi wa mumini alƙawarin zai ba shi a Aljanna ya fi duniya da duk abin da yake cikinta.

4. Duniya aljannar kafiri ce, kuma kurkukun mumini.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa masu da'awar cewa sun bar addini ne saboda kare rayuwar duniya cewa, ko da a ce babu wani abu na cutarwa da zai biyo baya idan suka yi hakan, to da aiki da hankali kaɗai ya isa ya sanya su su fifita lahirarsu a kan duniya. To ina kuma a ce wata azaba za ta biyo bayan abin da suka zaɓa na duniya suka bar na lahira?!

Suratul Kasas (60-61)
وَمَآ أُوتِيتُم مِّن شَيۡءٖ فَمَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَزِينَتُهَاۚ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ خَيۡرٞ وَأَبۡقَىٰٓۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٦٠ أَفَمَن وَعَدۡنَٰهُ وَعۡدًا حَسَنٗا فَهُوَ لَٰقِيهِ كَمَن مَّتَّعۡنَٰهُ مَتَٰعَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا ثُمَّ هُوَ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ مِنَ ٱلۡمُحۡضَرِينَ ٦١

60. Kuma duk irin abin da aka ba ku, to jin daɗin rayuwar duniya ne da adonta. Abin da yake wurin Allah kuwa (shi) ya fi alhairi ya fi kuma wanzuwa. Yanzu ba kwa hankalta ba?

61. Yanzu wanda Muka yi wa alƙawari kyakkyawa da zai same shi, zai zama kamar wanda Muka jiyar da shi daɗin rayuwar duniya, sannan kuma shi yana daga waɗanda za a kai su wuta a ranar alƙiyama?

Bayan da mushirikai suka ba da hanzarinsu na rashin karɓar Musulunci da cewa suna jin tsoron kada maƙiyansu su haɗu a kansu su yaƙe su ko kuma su yanke alaƙar kasuwanci da su, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa duk wani abu da zai ba su, to abu ne da za su more shi a nan duniya su yi ado da shi sannan daga ƙarshe ya gushe ko ya ƙare. To amma tanadin da ya yi musu a lahira na kyakkyawan sakamako shi ne ya fi musu alheri da wanzuwa a kan duk wani ƙyale-ƙyale na duniya.

Sai kuma ya tabbatar da haka ta hanyar jan hankalin masu hankali da su duba su gani, wane ne ya fi morewa da samun alheri tsakanin wanda ya yi wa kyakkyawan alƙawarin gidan Aljanna da ni'imominta waɗanda ido bai taɓa gani ba, kunne bai taɓa ji ba, zuciya kuma ba ta taɓa tunanin su ba, matuƙar ya yi wa Allah ɗa'a ya yi aiki nagari, idan an haɗa shi da wanda Allah ya jiyar da shi daɗin rayuwar duniya ya manta da aiki nagari bai miƙa wuya ga abin da manzanni suka zo da shi ba har ya mutu a kan haka, sannan a ranar alƙiyama ya tsinci kansa cikin waɗanda za a kai su wutar Jahannama?!

An karɓo daga Al-Mustaurid ɗan Shaddad (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Na rantse da Allah, duniya idan aka kwatanta ta da lahira ba komai ba ce face kamar ɗayanku ne ya tsoma ɗan yatsansa a cikin kogi, to sai ya duba ya ga me zai fito da shi?" [Muslim #2858].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tambayoyin da za a yi wa halittu a ranar alƙiyama, waɗanda suka haɗa da bautar Allah da kuma amsa kiran manzanninsa. Wannan shi ne ma'anar Kalmar Shahada.

2. A ranar alƙiyama ne waɗanda suka bauta wa wasu ba Allah ba za su gane sun bauta wa banza, domin babu abin da za su tsinana musu a ranar sai dai takaici da nadama.

3. A ranar alƙiyama gaskiya ce kaɗai za ta yi halinta; maɓarnaci zai tona wa kansa asiri da kansa, ya yi wa kansa mummunar shaida.

4. Tuba ta gaskiya tana kankare laifukan da suka gabace ta.

Suratul Kasas (62-67)
وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ أَيْنَ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ﴿٦٢﴾ قَالَ ٱلَّذِينَ حَقَّ عَلَيْهِمُ ٱلْقَوْلُ رَبَّنَا هَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ أَغْوَيْنَآ أَغْوَيْنَٰهُمْ كَمَا غَوَيْنَا ۖ تَبَرَّأْنَآ إِلَيْكَ ۖ مَا كَانُوٓاْ إِيَّانَا يَعْبُدُونَ ﴿٦٣﴾ وَقِيلَ ٱدْعُواْ شُرَكَآءَكُمْ فَدَعَوْهُمْ فَلَمْ يَسْتَجِيبُواْ لَهُمْ وَرَأَوُاْ ٱلْعَذَابَ ۚ لَوْ أَنَّهُمْ كَانُواْ يَهْتَدُونَ ﴿٦٤﴾ وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ مَاذَآ أَجَبْتُمُ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٦٥﴾ فَعَمِيَتْ عَلَيْهِمُ ٱلْأَنۢبَآءُ يَوْمَئِذٍ فَهُمْ لَا يَتَسَآءَلُونَ ﴿٦٦﴾ فَأَمَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَعَسَىٰٓ أَن يَكُونَ مِنَ ٱلْمُفْلِحِينَ ﴿٦٧﴾

62. Kuma ka tuna ranar da (Allah) zai kirawo su sai Ya ce: "Ina abokan tarayyar nawa waɗanda kuka kasance kuna riyawa?"

63. Sai waɗanda alƙawarin Allah (na azaba) ya tabbata a kansu su ce: "Ya Ubangijinmu, waɗannan da muka ɓatar, mun ɓatar da su ne kamar yadda mu ma muka ɓata; ba ruwanmu da kowa sai kai; don kuwa ba su kasance mu suke bauta wa ba."

64. Kuma aka ce: "Ku kirawo abokan tarayyar naku", sannan suka kirawo su, sai ba su amsa musu ba, suka kuma ga azaba. (Suka riƙa burin) ina ma sun kasance shiryayyu!

65. (Ka tuna) kuma ranar da (Allah) zai kirawo su sannan Ya ce: "Me kuka amsa wa manzanni (da shi?)"

66. Sai abubuwan da za su faɗa suka ɓace musu a wannan ranar, don haka su ba za su iya tambayar junansu ba.

67. To amma wanda ya tuba ya kuma yi imani ya kuma yi aiki nagari, to ana fatan ya zama cikin masu samun babban rabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin wulaƙancin da zai sami kafirai a ranar alƙiyama lokacin da zai kirawo su ya tambaye su, ina ababen tarayyarsa da suka riƙa bauta musu a duniya suna riya cewa su ababen tarayya ne ga Allah, me ya sa a yau ba za su amfane su da komai ba?
Sai shugabannin kafirai waɗanda azaba ta tabbata a kansu su kirawo Ubangiji su nuna mabiyansu su ce waɗannan ne suka ɓatar kamar yadda su ma suka dulmiya cikin ɓata. Sai su nesanta kansu daga mabiyansu, su nuna su allambaran ba su suke bauta wa ba, suna dai bauta wa shaiɗanu ne kawai.
Sai a umarci mushirikai da su kirawo ababen tarayyarsu waɗanda suke cewa za su cece su a lahira, sai su kirawo su domin su cece su daga azabar Allah da wulaƙancin da suke ciki, to amma sai su ji shiru ba su amsa musu kiran su ba, to a nan ne za su ga azabar Allah muraran sai su riƙa burin ina ma a duniya sun kasance shiryayyu?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a wannan rana za a tambaye su me suka amsa wa manzanni da shi lokacin da Allah ya aiko su zuwa gare su? To sai abubuwan da za su faɗa don tsayar da hujja da kare kai suka ɓace musu, suka kasa furta komai, suka kuma kasa tambayar junansu saboda tsananin rikicewa da jin tabbas ba makawa sai sun tafi wuta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci halin da muminai suke ciki a wannan rana, da cewa duk wanda ya tuba ya bar haɗa Allah da wani ya yi imani da Allah da manzanninsa, ya kuma yi kyakkyawan aiki, to wannan tabbas yana daga cikin masu rabauta da samun abin da suke nema, masu tsira daga duk wani abin ban tsoro.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ne kaɗai yake da haƙƙin zaɓar wanda ya ga dama ya ba shi matsayin da ya ga damar ba shi, domin kuwa shi ne ya halicci kowa da komai, don haka shi ne mai iko a kan komai.

2. Ilimin Allah ya game kowa da komai.

3. Kwaɗaitarwa a kan tsarkake niyya ga Allah shi kaɗai domin yana sane da abin da kowa ya ɓoye a zuciyarsa.

4. Kwaɗaitarwa a kan yawaita godiya da yabo ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Hukuncin Allah mai zartuwa ne babu mai ja da shi a kan duk abin da ya hukunta.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffantu da duk wasu siffofi na kamala, ya kuma tsarkaka daga duk wasu siffofi na tawaya da aibu.

Suratul Kasas (68-70)
وَرَبُّكَ يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُ وَيَخۡتَارُۗ مَا كَانَ لَهُمُ ٱلۡخِيَرَةُۚ سُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٦٨ وَرَبُّكَ يَعۡلَمُ مَا تُكِنُّ صُدُورُهُمۡ وَمَا يُعۡلِنُونَ ٦٩ وَهُوَ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ لَهُ ٱلۡحَمۡدُ فِي ٱلۡأُولَىٰ وَٱلۡأٓخِرَةِۖ وَلَهُ ٱلۡحُكۡمُ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٧٠

68. Kuma Ubangijinka Yana halittar abin da Ya ga dama Yana kuma zaɓar (abin da Ya ga dama). Ba su suke da zaɓi ba. Tsarki ya tabbata ga Allah kuma Ya ɗaukaka daga abin da suke yin shirka (da shi).

69. Kuma Ubangijinka Ya san abin da zukatansu suke ɓoyewa da kuma abin da suke bayyanawa.

70. Kuma Shi ne Allah, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; yabo ya tabbata a gare Shi a duniya da lahira; hukunci kuma nasa ne, kuma zuwa gare Shi ne kawai za a mayar da ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa cewa shi ne yake halittar abin da ya ga dama yake kuma zaɓar wanda ya ga dama ya datar da shi ga yi masa ɗa'a, kuma ya zaɓi wanda ya ga dama ya ba shi annabta. Su kuma mushirikai ba su da wani zaɓi nasu na kansu ballantana ma su yi wa Allah shisshigi cikin abin da ya zaɓa, ko kuma su zaɓo masa kishiyoyi suna bauta musu, alhali kuwa Allah bai ba wa wani mahaluƙi wannan haƙƙi ba. Don haka Allah ya tsarkaka ya kuma ɗaukaka daga duk wani abu da kafirai suke tara shi da shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa yana sane da duk abin da zukatan bayinsa suke ɓoyewa da abin da suke bayyanawa, babu abin da yake ɓoyuwa a gare shi, kuma zai yi wa kowa sakayyar da ta dace da shi.
Sai ya tabbatar da cewa shi ne Allah wanda babu wani abin bauta wa da gaskiya sai shi. Yabo da godiya da kirari kuma sun tabbata a gare shi a nan duniya da kuma lahira. Shi ne kuma wanda idan ya zartar da hukunci to ya zauna babu mai iya ja da shi a kansa, kuma duk halittu zuwa gare shi za a mayar da su ranar alƙiyama don ya yi wa kowa hukunci a kan ayyukansa masu kyau ko munana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samuwar dare da rana yana daga cikin manyan ni'imomin Allah ga bayinsa da suke nuna cikakkiyar rahamarsa a gare su da ya wajaba su gode masa.

2. Ya wajaba a kan bawa har kullum ya riƙa la'akari da ni'imomin da Allah ya yi masa, ya kuma kwatanta su da yanayin rashinsu; domin duk sanda zai kwatanta yanayin samuwarsu da na rashinsu to zai gane girman ni'imar da yake ciki. Amma idan yana ganin abin kamar wata al'ada ce ta yau da gobe wadda har abada ba za ta gushe ba, zuciyarsa ta makance ba ya jin tsananin buƙatuwarsa ga mahaliccinsa, to wannan ba zai haifar masa tunanin yi wa Allah godiya a kan ni'imominsa ba.

3. Dare da rana wasu ni'imomi ne da ɗan'adam yake matuƙar buƙatarsu a rayuwarsu ta duniya, domin yana da buƙatar fita neman abin da zai kai bakinsa, hakan kuwa ba zai yiwu ba sai a cikin hasken yini, don haka yake da tsananin buƙatarsu. Hakanan ba zai samu ƙarfin fita neman arzukinsa ba sai jikinsa yana samun hutu da daddare, babu kuma mai iya samar masa da daren nan sai Allah.

4. Kyan tsarin zubin Alƙur'ani, lokacin da Allah ya yi maganar dare sai ya ce: "To me ya sa ba kwa ji?" Domin ji ne ya fi amfani da daddare. Amma lokacin da ya yi maganar rana sai ya ce: "Me ya sa ba kwa gani?" Domin gani ya fi amfani da rana.

Suratul Kasas (71-73)
قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيۡكُمُ ٱلَّيۡلَ سَرۡمَدًا إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ مَنۡ إِلَٰهٌ غَيۡرُ ٱللَّهِ يَأۡتِيكُم بِضِيَآءٍۚ أَفَلَا تَسۡمَعُونَ٧١ قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيۡكُمُ ٱلنَّهَارَ سَرۡمَدًا إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ مَنۡ إِلَٰهٌ غَيۡرُ ٱللَّهِ يَأۡتِيكُم بِلَيۡلٖ تَسۡكُنُونَ فِيهِۚ أَفَلَا تُبۡصِرُونَ٧٢ وَمِن رَّحۡمَتِهِۦ جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ لِتَسۡكُنُواْ فِيهِ وَلِتَبۡتَغُواْ مِن فَضۡلِهِۦ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ٧٣

71. Ka ce: "Ku ba ni labari, (yanzu) idan Allah Ya sanya muku dare tutur har zuwa ranar alƙiyama, wane abin bauta ne ba Allah ba zai zo muku da wani haske? To me ya sa ba kwa ji?"

72. Ka ce: “Ku ba ni labari, (yanzu) idan Allah Ya sanya muku rana tutur har zuwa ranar alƙiyama, wane abin bauta ne ba Allah ba zai zo muku da dare da za ku samu nutsuwa a cikinsa? To me ya sa ba kwa gani?”

73. Daga rahamarsa ne kuma Ya sanya muku dare da rana don ku samu nutsuwa a cikinsa (wato dare) kuma don ku nema daga falalarsa (da rana), don kuma ku riƙa yin godiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu daga cikin ni’imominsa ga bayinsa waɗanda ya wajaba su kalle su, su kuma gode masa a kansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa ya faɗa wa mushirikai cewa su ba shi labari cewa, idan Allah ya mayar musu da dare tutur har zuwa ranar alƙiyama ba tare da yankewa ba, to wane abin bauta ne ba Allah ba wanda zai kawo musu wani haske kamar na rana? Ya kuma tambaye su cewa me ya sa ba sa sauraron waɗannan hujjoji da ake kawo musu su fahimci cewa babu wani abin bauta da zai iya kawo musu waɗannan abubuwa?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar Manzonsa (ﷺ) ya tambaye su su ba shi labari, idan ya mayar musu da yini tutur, watau rana diman-da’iman har zuwa ranar alƙiyama ba tare da yankewa ba, wane abin bauta ne ba Allah ba da zai zo musu da wani dare wanda za su samu nutsuwa a cikinsa su huta daga wahalhalun aiki da suka yi fama da shi da rana? Ya kuma tambaye su cewa me ya sa ba za su dubi waɗannan ayoyi ba su gane cewa babu wani abin bauta da zai iya kawo musu waɗannan in ba Allah ba?
Sai ya tabbatar musu da cewa daga cikin rahamarsa ne ga mutane ya halitta musu dare mai duhu don su samu su huta a cikinsa bayan sun sha wahalhalun aiki da rana, ya kuma halitta musu yini mai haske domin su fita neman arziki a cikinsa, don kuma su gode wa ni’imomin Allah a gare su, su guje wa butulce masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabawa su ne za su ba da shaida a kan al'ummunsu game da saƙon da Allah ya aiko su da shi zuwa gare su.

2. A ranar alƙiyama duk wata ƙarya za ta bayyana, gaskiya ce kaɗai za ta amfanar da mai ita.

Suratul Kasas (74-75)
وَيَوۡمَ يُنَادِيهِمۡ فَيَقُولُ أَيۡنَ شُرَكَآءِيَ ٱلَّذِينَ كُنتُمۡ تَزۡعُمُونَ ٧٤ وَنَزَعۡنَا مِن كُلِّ أُمَّةٖ شَهِيدٗا فَقُلۡنَا هَاتُواْ بُرۡهَٰنَكُمۡ فَعَلِمُوٓاْ أَنَّ ٱلۡحَقَّ لِلَّهِ وَضَلَّ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ ٧٥

74. Ka kuma (tuna) ranar da (Allah) zai kirawo su, sai Ya ce: “Ina abokan tarayyar nawa waɗanda kuka kasance kuna riyawa?”

75. Muka kuma ware wani shaida daga kowacce al’umma (wato annabinsu) sai Muka ce: “To ku kawo dalilinku (na yin tarayya da Allah).” Sai suka san cewa lalle gaskiya tana ga Allah, kuma abin da suka kasance suna ƙirƙira ya ɓace musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake nuna wa mushirikai cewa bautar wanin Allah da suke yi son zuciya ne ƙarara amma ba wani dalili suke da shi mai ƙarfi ba. Allah ya tunatar da su ranar alƙiyama ranar da zai kirawo su ya tambaye su, ina abubuwan da suke bauta wa a duniya suna riya cewa abokanan tarayyarsa ne, sai su zo su kuɓutar da su daga azabar Allah a gare su a wannan ranar.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa idan an halarto da kowace al’umma da abubuwan da suka bauta wa ba Allah ba, sai ya ware wani mai ba da shaida daga cikin kowace al’umma, watau annabinsu da

Allah ya aika musu, domin ya ba da shaida a kan kafircinsu da ƙaryata manzanni da suka yi. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya neme su da su kawo hujjarsu ta bautar wasu ba Allah ba da kuma hujjarsu ta ƙaryata manzanninsa. To a nan ne za su tabbatar da cewa Allah ne mai gaskiya shi kaɗai, sai kuma su nemi abubuwan da suka ƙirƙira suna bauta musu su rasa su, domin sun ɓace musu ɓat ba ɗuriyarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan dukiya da jahilci suka haɗu wuri ɗaya to ba ƙaramar ɓarna suke haifarwa ba.

2. Fariya da girman kai saboda an mallaka wa mutum arzikin duniya mummunar halayya ce da Allah yake fushi da ita.

3. Musulunci bai haramta wa mutum ya mori amfanin dukiyarsa ta hanyar da Allah ya halatta masa ba, amma dole ne ya yi hattara kada yin hakan ya hana shi neman lahira da dukiyarsa.

4. Duk wanda ya sami kansa cikin wata ni'ima ta duniya, to kada ya manta da cewa Allah ne ya ga dama ya yi masa wannan tagomashi, don haka shi ma ya kyautata wa wasu domin ni'imarsa ta ɗore.

5. Wajibi ne a yi nasiha ga duk wanda aka fuskanci ya ɗauko hanyar lalacewa komai girmansa cikin al'umma.

6. Duk wata ni'ima da ɗan'adam yake ciki to yin Allah ne da zaɓinsa, ba ƙoƙarin mutum ba ne ko ƙwarewarsa.

7. Duk ƙarfin mutum ko yawan arzikinsa ko ƙarfin mulkinsa, to Allah yana sama da shi; idan ya ja da Allah to zai sha ƙasa.

Suratul Kasas (76-78)

*إِنَّ قَٰرُونَ كَانَ مِن قَوۡمِ مُوسَىٰ فَبَغَىٰ عَلَيۡهِمۡۖ وَءَاتَيۡنَٰهُ مِنَ ٱلۡكُنُوزِ مَآ إِنَّ مَفَاتِحَهُۥ لَتَنُوٓأُ بِٱلۡعُصۡبَةِ أُوْلِي ٱلۡقُوَّةِ إِذۡ قَالَ لَهُۥ قَوۡمُهُۥ لَا تَفۡرَحۡۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡفَرِحِينَ ٧٦ وَٱبۡتَغِ فِيمَآ ءَاتَىٰكَ ٱللَّهُ ٱلدَّارَ ٱلۡأٓخِرَةَۖ وَلَا تَنسَ نَصِيبَكَ مِنَ ٱلدُّنۡيَاۖ وَأَحۡسِن كَمَآ أَحۡسَنَ ٱللَّهُ إِلَيۡكَۖ وَلَا تَبۡغِ ٱلۡفَسَادَ فِي ٱلۡأَرۡضِۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ٧٧ قَالَ إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلۡمٍ عِندِيٓۚ أَوَ لَمۡ يَعۡلَمۡ أَنَّ ٱللَّهَ قَدۡ أَهۡلَكَ مِن قَبۡلِهِۦ مِنَ ٱلۡقُرُونِ مَنۡ هُوَ أَشَدُّ مِنۡهُ قُوَّةٗ وَأَكۡثَرُ جَمۡعٗاۚ وَلَا يُسۡـَٔلُ عَن ذُنُوبِهِمُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٧٨

76. Lalle Karuna yana daga mutanen Musa, sai ya yi musu girman kai, Muka kuma ba shi taskokin (dukiya) wadda lalle makullansu suna yi wa tarin jama'a ƙarfafa nauyin (ɗauka), yayin da mutanensa suka ce da shi: "Kada ka yi fariya, lalle Allah ba Ya son masu fariya.

77. "Kuma ka nemi gidan lahira ta hanyar abin da Allah Ya ba ka; kada kuma ka manta rabonka na duniya; kuma ka kyautata kamar yadda Allah Ya kyautata maka, kada kuma ka nemi yin ɓarna a bayan ƙasa. Lalle Allah ba Ya son masu ɓarna."

78. Ya ce: "Ai ni an ba ni ita (wato dukiyar) ta hanyar ilimin da nake da shi ne." Shin yanzu bai sani ba ne cewa haƙiƙa Allah Ya hallaka wasu al'ummun da suke a gabaninsa waɗanda suka fi shi ƙarfi da kuma yawan tarin (dukiya)? Ba kuwa za a tambayi masu laifi game da laifukansu ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin wani ƙasurgumin ƙafiri da ya yi zamani da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ana kiran sa Karuna, wanda yana daga cikin mutanen Annabi Musa, watau Banu Isra'ila, sai dai da alama yana da ƙaƙƙarfar alaƙa da fadar Fir'auna da jama'arsa, don haka suka buɗa masa damammaki na tara ƙazamar dukiya wadda shi ma kansa bai san iyakar yawanta ba, sai ya riƙa taskace ta a wurare da gine-gine daban-daban, ya kuma tanadi makullai yana kulle waɗannan taskoki nasa. Watau saboda yawan waɗannan makullai sai an tara ƙatti majiya ƙarfi suke iya ɗaukar su, amma fa da kyar saboda tsananin nauyinsu da yawansu.
Ganin irin wannan maɗuɗuwar dukiya da Allah ya mallaka wa Karuna sai ta sanya shi ya shiga nuna wa mutanensa ɗagawa da girman kai, yana wulaƙanta su yana cutar da su. Wannan ya sa masu hankali daga cikin jama'arsa suka shirya haɗuwa da shi don su yi masa nasiha, su ja hankalinsa game da haɗarin da yake ƙoƙarin jefa kansa ciki. Sun yi masa nasihohi har guda biyar:
Nasiha ta farko, sun ja kunnensa da yi masa gargaɗi a kan ya daina yi wa mutane fariya da homa saboda yawan dukiya da ya tara, domin kuwa Allah ba ya son masu irin wannan hali nasa, don haka ya guji janyo wa kansa fushin Allah da uƙubarsa.
Nasiha ta biyu, suka nuna masa ya nemi lada a wurin Allah da wannan dukiya da ya ba shi, domin sakamakon lahira shi ne mai ɗorewa har abada.
Nasiha ta uku, suka nuna masa cewa kada ya fahimci kamar suna umartar sa ne da ya kashe dukiyarsa duka wajen neman lahira; sai dai ya biya buƙatunsa na duniya ta hanyar amfani da dukiyarsa cikin abin da Allah ya halatta masa.
Nasiha ta huɗu, suka yi kira gare shi da ya kyautata wa mutane ta hanyar taimaka wa mabuƙata ya yawaita aikin alheri kamar yadda Allah ya kyautata masa ya ba shi wannan tarin dukiyar.
Nasiha ta biyar, suka kuma ja kunnensa da yi masa gargaɗi a kan ya daina yaɗa ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar saɓon Allah da zalunci da wulaƙanta mutane, domin Allah ba ya son ɓarna, don haka ya guji jawo wa kansa fushin Allah da uƙubarsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan Karuna ya ji duk waɗannan nasihohi daga bakin jama'arsa sai ya fara cika baki yana cewa, ai shi wannan dukiyar ba kowa ne ya ba shi ita ba sai iliminsa, watau saninsa da ƙwarewa da harkokin kasuwanci da neman kuɗi su suka ba shi damar ya tara dukiyarsa. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar masa da martani da cewa, yanzu shi Karuna duk ilimin da yake tutiya da shi bai san cewa a baya can an yi wasu al'ummu waɗanda suka fi shi ƙarfi da tara dukiya ba, amma da suka yi ɗagawa da butulce wa Ubangijinsu sai Allah ya hallaka su, yanzu ko ɗuriyarsu ma ba a ji? Lokacin kuma da Allah ya yi niyyar hallaka su, ya gama da su ne kawai ba tare da ya tsaya yi musu wasu tambayoyi a kan laifuffukansu ba balle ma ya saurari hanzarinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda Allah ya ba shi dukiya ya yi amfani da ita wajen lalata al'umma da yaɗa ɓarna to ya ɗauki hali ne irin na Karuna.

2. 'Yan duniya su ne suka fi sauƙin ruɗuwa da aukawa cikin fitina.

3. Falalar masu ilimi da nuna cewa su ne masu hikima da zurfin tunani da hangen nesa.

4. Falalar haƙuri da cewa shi ne yake yin jagoranci zuwa ga samun shiriya da dacewa cikin dukkan al'amura.

5. Girman kai da nuna isa a bayan ƙasa ƙarshen mai yin sa shi ne halaka da taɓewa duniya da lahira.

6. Samun arziki na duniya ba shi yake nuna mutum ya zama nagari ba a wurin Allah.

7. Hallakar Karuna uƙuba ce gare shi a kan mummunan aikinsa, sannan izina ce da wa’azi ga waninsa.

8. Duk masu nuna isa da girman kai a bayan ƙasa ko maɓarnata a cikinta ba su da wani rabo a gidan lahira.

9. Yalwar falalar Allah da kuma cikar adalcinsa yayin da yake ninka sakamakon mumini wanda ya yi aiki nagari, amma wanda ya yi mummunan aiki to yana saka masa ne daidai da aikinsa, ba ya ƙara masa komai na laifin da bai aikata ba.

Suratul Kasas (79-83)
فَخَرَجَ عَلَىٰ قَوۡمِهِۦ فِي زِينَتِهِۦۖ قَالَ ٱلَّذِينَ يُرِيدُونَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا يَٰلَيۡتَ لَنَا مِثۡلَ مَآ أُوتِيَ قَٰرُونُ إِنَّهُۥ لَذُو حَظٍّ عَظِيمٖ ٧٩ وَقَالَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ وَيۡلَكُمۡ ثَوَابُ ٱللَّهِ خَيۡرٞ لِّمَنۡ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗاۚ وَلَا يُلَقَّىٰهَآ إِلَّا ٱلصَّٰبِرُونَ ٨٠ فَخَسَفۡنَا بِهِۦ وَبِدَارِهِ ٱلۡأَرۡضَ فَمَا كَانَ لَهُۥ مِن فِئَةٖ يَنصُرُونَهُۥ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُنتَصِرِينَ ٨١ وَأَصۡبَحَ ٱلَّذِينَ تَمَنَّوۡاْ مَكَانَهُۥ بِٱلۡأَمۡسِ يَقُولُونَ وَيۡكَأَنَّ ٱللَّهَ يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦ وَيَقۡدِرُۖ لَوۡلَآ أَن مَّنَّ ٱللَّهُ عَلَيۡنَا لَخَسَفَ بِنَاۖ وَيۡكَأَنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ٨٢ تِلۡكَ ٱلدَّارُ ٱلۡأٓخِرَةُ نَجۡعَلُهَا لِلَّذِينَ لَا يُرِيدُونَ عُلُوّٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فَسَادٗاۚ وَٱلۡعَٰقِبَةُ لِلۡمُتَّقِينَ ٨٣

79. Sai ya fito wa mutanensa a cikin adonsa; sai waɗanda suke burin rayuwar duniya suka ce: “Ina ma da za mu mallaki irin abin da aka bai wa Karuna? Lalle shi mai babban rabo ne.”

80. Waɗanda kuwa aka bai wa ilimi sai suka ce: “Kaiconku, ai ladan Allah shi ya fi alheri ga wanda ya yi imani, ya kuma yi aiki na gari. Ba kuwa wanda ake yi wa katari da shi sai masu haƙuri.”

81. Sannan muka kifar da shi (Karuna) tare da gidansa cikin ƙasa, kuma ba shi da wata jama’a da za su taimake shi ba Allah ba, kuma bai kasance daga masu taimaka wa kawunansu ba.

82. Kuma waɗanda suka yi burin matsayinsa a jiya suka wayi gari suna cewa: “Wai, yau mun ga abin al’ajabi! Allah Yana yalwata arziki ga wanda Ya ga dama daga bayinsa, Yana kuma ƙuntatawa ga wanda Ya ga dama; ba don Allah Ya ba mu sa’a ba da mu ma Ya kifar da mu. Wai, abin mamaki, lalle kafurai ba sa rabauta!”

83. Wancan gida na lahira Muna ba da shi ga waɗanda ba sa nufin girman kai da ɓarna a bayan ƙasa. Kyakkyawan ƙarshe kuma yana ga masu kiyaye dokokin Allah ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Karuna ya yi watsi da nasihohin da aka yi masa, ya ci gaba da ɗagawarsa da sheƙe ayarsa. Wata rana ya shirya fita rangadi cikin jama’arsa, ya fita tare da jama’arsa cikin kwalliya ta ƙasaita har ya ja hankalin Banu Isra’ila suka kasu gida biyu:
Kashi na farko, su ne gama-garin mutane marasa ilimi waɗanda suka kiɗime da ganin irin wannan sheƙe-aya da Karuna yake yi da dukiyarsa, suka fara burin ina ma su ma su samu dukiya mai yawa irin tasa, domin suna ganin shi kam ya dace da babban rabo a duniya.
Kashi na biyu kuwa su ne masu ilimin cikinsu masu hankali da hangen nesa; su kam sun fahimci cewa duk wannan abu da Karuna yake yi ba komai ba ne sai ruɗin Shaiɗan, kuma jin daɗin duniya komai yawansa mai ƙarewa ne. Suka kuma yi Allah wadarai da abin da jahilai suke faɗa, suka nuna musu cewa sakamakon da Allah zai bayar a lahira da jin daɗin da ya tanada a ɗan ga duk wanda ya yi imani ya kuma yi aiki nagari ya fi duk wani ƙyale-ƙyale na duniya da aka ba wa Karuna yake bushasha a cikinsa. Amma ba kowa yake samun dacen faɗar irin wannan magana ba ko ya yi aiki da ita sai waɗanda suka yi haƙuri suka fifita sakamakon da ke wurin Allah a kan duk wani jin daɗi na nan duniya.

Yayin da Karuna yake tsakiyar sheƙe ayarsa ya kuma ruɗi wasu daga cikin mutanensa Banu Isra'ila har suka bi shi, sai kwatsam azabar Allah ta auka masa ba zato ba tsammani, Allah ya nutsar da shi har da gidansa da dukiyarsa a cikin ƙasa, kuma aka rasa waɗanda za su taimaka masa cikin jama'arsa da suke yi masa kanzagi da bayinsa masu tsaron sa, su kare shi daga azabar Allah, kuma shi kansa ba zai iya taimaka wa kansa da komai ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ganin irin wannan mummunan ƙarshe da Karuna ya faɗa ya sanya jahilan can da suka ruɗu da shi da farko suka dawo cikin hankalinsu, suka shiga sallallami da mamakin cewa ashe Allah ne yake ba da arziki ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, ya kuma ƙuntata wa wanda ya ga dama. Suka gane cewa ba don Allah ya yi musu baiwa da afuwarsa ba bai kama su da laifin maganganun da suka yi ba, to da su ma tuni ƙasa ta haɗiye su tare da Karuna. Suka yi mamaki matuƙa da yadda masu ƙafirce wa Allah ba sa rabauta a duniya ko a lahira, domin ga shi dai yadda Karuna ya zamanto aya a gare su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yana bayar da sakamakon gidan lahira da jin daɗinta ne kawai ga mutanen da ba sa yin girman kai da bijire wa imani da Allah da bin gaskiya a bayan ƙasa, kuma ba sa nufin ɓarna a cikinta; kyakkyawan ƙarshe kuma yana ga masu kiyaye dokokin Allah, domin su ne kaɗai za su rabauta da ni'imar Aljanna da kuma samun yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Sannan Allah ya tabbatar da cewa duk wanda ya zo masa ranar alƙiyama da kyakkyawan aiki, kamar salla da zakka da azumi da sadaka, to yana da sakamakon da ya fi wannan kyakkyawan aikin nasa, domin za a ninka masa shi goma zuwa ɗari bakwai zuwa ninkin ba-iyaka. Duk kuma wanda ya zo da mummunan aiki kamar kafirci da shirka da bidi'a da zina da sauransu, to ba za a saka wa mai mummunan aiki ba sai da kwatankwacin abin da ya aikata ba ƙari ba ragi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba ya daga cikin hikima ko kaɗan a ce Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya saukar da Alƙur'ani wanda ya ƙunshi bayani a kan halal da haram da hukunce-hukuncen abubuwan rayuwa gaba ɗaya, ya kuma bar mutane hakanan ba tare da mayar da su zuwa gare shi don yi musu hisabi a kan ayyukansu ba. Yin haka ya zama wasa da rashin kan gado abin da Allah ya tsarkaka daga gare su.

2. Saukar da Alƙur'ani ga Manzon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) rahama ce babba a gare shi da duniya baki ɗaya.

3. Haramcin taimaka wa ɓatattu a kan ɓatansu.

4. Wajabcin tsayuwa daram a kan addini da dagewa wajen kira zuwa ga Allah da isar da saƙonsa zuwa ga al'umma.

5. Umarni da riƙo da Tauhidi da nesantar duk wata hanya ta shirka.6. Komai na duniya mai gushewa ne ya bar Allah shi kaɗai mahalliccin kowa da komai.

Suratul Kasas (84-88)
مَن جَآءَ بِٱلۡحَسَنَةِ فَلَهُۥ خَيۡرٞ مِّنۡهَاۖ وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَلَا يُجۡزَى ٱلَّذِينَ عَمِلُواْ ٱلسَّيِّاٰتِ إِلَّا مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٨٤ إِنَّ ٱلَّذِي فَرَضَ عَلَيۡكَ
ٱلۡقُرۡءَانَ لَرَآدُّكَ إِلَىٰ مَعَادٖۚ قُل رَّبِّيٓ أَعۡلَمُ مَن جَآءَ بِٱلۡهُدَىٰ وَمَنۡ هُوَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٨٥ وَمَا كُنتَ تَرۡجُوٓاْ أَن يُلۡقَىٰٓ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبُ إِلَّا رَحۡمَةٗ مِّن
رَّبِّكَۖ فَلَا تَكُونَنَّ ظَهِيرٗا لِّلۡكَٰفِرِينَ ٨٦ وَلَا يَصُدُّنَّكَ عَنۡ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ بَعۡدَ إِذۡ أُنزِلَتۡ إِلَيۡكَۖ وَٱدۡعُ إِلَىٰ رَبِّكَۖ وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ٨٧
وَلَا تَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَۘ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ كُلُّ شَيۡءٍ هَالِكٌ إِلَّا وَجۡهَهُۥۚ لَهُ ٱلۡحُكۡمُ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٨٨

84. Duk wanda ya zo da kyakkyawan aiki, to yana da (lada) fiye da aikinsa; wanda kuma ya zo da mummunan aiki, to ba za a saka wa waɗanda suka aikata munanan ayyuka ba face daidai da abin da suka kasance suna aikatawa.

85. Lalle Wanda Ya saukar maka da Alƙur'ani tabbas zai mayar da kai zuwa makoma. Ka ce: "Ubangijina Shi Ya san wanda ya zo da shiriya da kuma wanda yake cikin ɓata mabayyani."

86. Kuma ba ka kasance kana fatan a saukar maka da littafi ba, sai dai (an yi haka ne) don rahama daga Ubangijinka; to don haka kada ka zamanto mai taimakon kafirai.

87. Kuma lallai kada su hana ka (isar da) ayoyin Allah bayan an riga an saukar maka da su; kuma ka yi kira zuwa ga Ubangijinka; kuma lallai kada ka zamanto daga mushrikai.

88. Kuma kada ka bauta wa wani abin bauta daban tare da Allah. Babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. Kowane abu mai halaka ne sai Fuskarsa kawai. Hukunci (duk) nasa ne, zuwa gare Shi kuma za a mayar da ku.

A ayoyin ƙarshe na wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, Ubangijinsa wanda ya saukar masa da Alƙur'ani ya kuma ɗora masa nauyin karantar da shi da aiki da hukunce-hukuncensa, lalle zai mayar da shi mahaifarsa, watau Makka.
Idan mun dubi wannan Sura a matsayinta na kasancewarta *Makkiyya* gaba ɗayanta, wannan kamar nuni ne Allah yake yi wa Manzonsa (ﷺ) cewa za a fitar da shi daga garin Makka zuwa inda zai yi hijira, amma kuma Allah zai ɗawo da shi zuwa mahaifarsa. Hasali ma shi kansa Annabi an nuna masa a mafarki garin da zai yi hijirar zuwa gare shi cewa, gari ne mai bishiyoyin dabino, kamar yadda ya zo a cikin Sahihul Bukhari [#3905] da Muslim [#2473].

Sannan kuma Waraƙatu ɗan Naufal ya sanar da shi cewa, mutanen Makka za su fitar da shi daga mahaifarsa. [Dubi Bukhari #3 da Muslim #160]. Annabi (ﷺ) kuma bai manta da wannan ba.
Wasu malaman tafsiri sun fassara ayar da cewa Allah yana sanar da Manzonsa (ﷺ) cewa kamar yadda ya saukar masa da Alƙur'ani hakanan kuma zai mayar da shi makomarsa ta ƙarshe, watau Aljanna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya faɗa wa mushirkai masu ganin sa a kan ɓata cewa, Ubangijinsa shi ya fi sanin wanda ya zo da shiriya da kuma wanda yake cikin ɓata bayyananne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da shi irin falala da ni'ima da ya yi masa wadda ba ya tsammaninta, watau saukar masa da Alƙur'ani. Allah ya yi masa haka ne domin nuna masa rahamarsa a gare shi, don haka ya gargaɗe shi da cewa kada ya kuskura ya zamanto mai taimaka wa kafirai a kan ɓatansu, kuma kada ya yarda mushirkai su hana shi isar da saƙon ayoyin da aka riga aka saukar masa, ya tashi ya ci gaba da kira zuwa ga Ubangijinsa da yin imani da shi da aiki da shari'arsa. Kuma kada ya zamanto daga cikin masu shirka da Allah; ya kasance tare da muminai masu kaɗaita Allah da bauta.
Sai kuma ya sake yi masa wani hani a kan kiran wani da bauta masa tare da Allah, saboda babu wani abin bauta na gaskiya sai Allah shi kaɗai, kuma komai na duniyar nan zai hallaka ya gushe sai Allah kaɗai shi ne mai wanzuwa; rayayye wanda da ba zai mutu ba har abada. Hukunci kuma duk nasa ne a duniya da lahira, kuma zuwa gare shi ake komar da kowa da komai domin ya yi wa bayinsa hisabi a kan ayyukan da suka aikata masu kyau da munana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sanin cikakkiyar hikimar Allah wanda ya zartar da cewa ba zai ƙyale mumini ba don ya nuna imaninsa da fatar bakinsa har sai ya jarraba gaskiyar imanin nasa don ya bayyana ƙarfinsa ko rauninsa a zuciyarsa. Ta haka ne za a bambance tsakanin masu gaskiya da maƙaryata masu cika baki. Allah yakan yi jarrabawarsa ta hanyoyi daban-daban, kamar ta hanyar wadata da talauci, ko yalwa ko ƙunci ko zaman lafiya ko tashe-tashen hankula.

2. Jarrabar Allah ga muminai daɗaɗɗiyar sunnarsa ce da ta gudana a cikin al'ummun da suka gabata.

3. Abin da yake sanya wasu dogewa a kan sabon Allah da aikata miyagun laifuka shi ne zaton da suke yi na cewa za su iya kauce wa azabar Allah. Wannan babu shakka mummunan hukunci ne da Shaiɗan ya raɗa musu.

29-Suratul Ankabut

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da '*Suratul Ankabut* '. *Al-Ankabut* yana nufin gizogizo, wanda aka ambace shi a cikinta a aya ta 41.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai suna ganin Sura ce *Makkiyya*. An sami saɓani a kan ayoyinta goma sha ɗaya na farko, wasu malamai suna ganin sun sauka ne a Madina, domin an buɗe Surar da magana da muminai da yin gargaɗi a kan munafunci a aya ta 11; munafunci kuwa ya ɓullo ne a Madina ba a Makka ba.
Daga ayoyinta kuma za a iya fahimtar kasancewarta *Makkiyya*, domin a ciki Allah ya yi magana a kan kafirai da batun mu'ujizar Alƙur'ani da bayyana ƙissoshin wasu annabawa domin ɗaukar izina da darasi da batun azabar lahira ga masu girman kai masu bijire wa gaskiya.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin da biyar (85) a jerin saukar surori, ta sauka bayan *Suratur Rum* gabanin *Suratul Muɗaffifin*. Tana cikin surorin ƙarshe da suka sauka a Makka kafin hijira.

4. Adadin ayoyinta:
Duk malamai sun haɗu a kan cewa adadin ayoyinta sittin da tara (69) ne.

5. Babban Jigonta:
Surar tana nuna cewa imani ba kalma ce da ake faɗar ta da fatar baki kawai ba. Imani yana buƙatar haƙuri da juriya a kan abin da mumini zai fuskanta na fitintinu da tsangwama saboda imaninsa, don haka yana buƙatar jajircewa har ya kai ga cin nasara.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tabbatar da muminai waɗanda mushirikai suke ta fitinar su don ƙoƙarin hana su addinin Musulunci.
• Alƙawarin Allah na taimakon muminai da wulaƙanta mushirikai da mataimakansu daga cikin ma'abota littafi.
• Umarni a kan nisantar mushirikai ko da kuwa makusanta ne.
• Wajabcin yin haƙuri a kan cutarwar mushirikai da nuna wa muminai cewa ƙasar Allah tana da yalwa, suna iya yin hijira domin tsira da addininsu.
• Jayayya da ma'abota littafi ta hanyar da ta dace in ban da waɗanda suke zaluntar muminai daga cikinsu.
• Umarni ga Annabi (ﷺ) a kan ya dage wajen isar da saƙon Alƙur'ani da shari'un Musulunci.
• Ɗaukan darasi daga al'ummu da manzanninsu da suka gabata da bayanin cewa shi ma Manzon Allah (ﷺ) ya zo ne da irin abin da sauran manzanni suka zo da shi.

• Kafa dalili mai ƙarfi a kan cewa Alƙur’ani saukakke ne daga Allah, idan aka lura da cewa Annabi mutum ne ummiyyi ba ya rubutu ba ya karatu.
• Tunatar da mushirikai irin ni’imomin da Allah ya yi musu domin su watsar da bautar wasu gumaka ba Allah ba, su bauta wa Allah shi kaɗai wanda suka yarda da cewa shi ne mahaliccin kowa da komai a sammai da ƙasa.
• Kafa hujja a kan yiwuwar tashi bayan mutuwa, domin ƙirƙirar halitta daga babu ya fi zama abin mamaki a kan sake dawo da ita bayan mutuwa.
• Tabbatar da sakamakon ayyuka a ranar alƙiyama.
• Bayar da misali na kafiran da suka riƙi wasu abubuwan bauta ba Allah ba da misalin gidan gizo-gizo mai matuƙar rauni.

Suratul Ankabut (1-4)
الٓمٓ ١ أَحَسِبَ ٱلنَّاسُ أَن يُتۡرَكُوٓاْ أَن يَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا وَهُمۡ لَا يُفۡتَنُونَ ٢ وَلَقَدۡ فَتَنَّا ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۖ فَلَيَعۡلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ صَدَقُواْ وَلَيَعۡلَمَنَّ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٣ أَمۡ حَسِبَ ٱلَّذِينَ يَعۡمَلُونَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن يَسۡبِقُونَاۚ سَآءَ مَا يَحۡكُمُونَ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ALIF LAM MIM.

2. Yanzu mutane suna tsammanin za a ƙyale su ne saboda suna cewa: “Mun yi imani,” kuma ba za a fitine su ba?

3. Haƙiƙa kuwa Mun fitini waɗanda suke gabaninsu; to tabbas kuwa Allah zai bayyana waɗanda suka yi gaskiya, lalle kuma zai bayyana maƙaryata.

4. Ko kuma waɗanda suke aikata munanan ayyuka suna tsammanin za su gagare Mu ne? Abin da suke hukuntawa ya munana.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da haruffa kamar yadda ya yi a wasu surori da suka gabace ta [Dubi farkon *Suratul Baƙara* a wannan tafsirin domin ƙarin bayani].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yanzu mutane za su yi tsammani a bar su hakanan ba a jarrabi gaskiyar imaninsu ba don kawai sun furta da baki cewa sun yi imani? Watau abin ba haka yake ba, lalle sai an jarraba su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ya jarrabi al'ummun da suka gabaci wannan al’umma, kuma yana yin haka ne domin ya rarrabe tsakanin masu gaskiya cikin da’awar imaninsu a fili a san su, da kuma maƙaryata.

An ƙarɓo daga Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Na tambayi Manzon Allahﷺ (ﷺ) cewa: Waɗanne mutane ne jarrabawarsu ta fi tsanani?” Sai ya ce: “Annabawa ne, sannan waɗanda suka fi kwatanta irin ayyukansu sannan masu biye da su. Akan jarrabi mutum gwargwadon addininsa, to idan addininsa mai ƙarfi ne sai jarrabawarsa ta fi tsananta, idan kuwa akwai sakaci a cikin addininsa sai a jarrabe shi gwargwadon ƙarfin addininsa. Jarraba ba za ta rabu da bawa ba har sai ta sanya shi yana tafiya a bayan ƙasa ba tare da wani zunubi a kansa ba.” [Tirmizi #2398 da Ahmad #1481].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kashedi ga masu miyagun ayyuka na kafirci da saɓon Allah, masu zaton za su gagare shi, ya nuna musu cewa wannan zaton banza da wofi ne suke yi kuma mummunan

hukunci suke yanke wa kawunansu, domin suna jayayya ne da ikon Allah da cikakkiyar Kudurarsa a kan komai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Albishir ga duk wani mumini mai kyakkyawan fatan haɗuwa da Ubangijinsa da cewa wannan ranar kusa take, don haka ya yi kyakkyawan tanadin haɗuwa da Ubangijinsa tare da kyakkyawan fata.

2. Allah mai cikakkiyar wadata ne, ba ya buƙatar komai daga halittunsa, don haka kowa ya yi aiki mai kyau ya yi ne don kansa, wanda ya yi mummuna shi ne zai cutu ba zai cuci Allah da komai ba.

3. Kyawawan ayyuka suna gusar da zunuban bawa.

Suratul Ankabut (5-7)

مَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ ٱللَّهِ فَإِنَّ أَجَلَ ٱللَّهِ لَأٓتٖۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٥ وَمَن جَٰهَدَ فَإِنَّمَا يُجَٰهِدُ لِنَفۡسِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَغَنِيٌّ عَنِ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُكَفِّرَنَّ عَنۡهُمۡ سَيِّـَٔاتِهِمۡ وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَحۡسَنَ ٱلَّذِي كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٧

5. Wanda ya zama yana fatan haɗuwa da Allah, to lalle lokacin (haɗuwa da) Allah tabbas mai zuwa ne. Kuma Shi ne mai ji, Masani.

6. Duk wanda kuwa ya yi jihadi, to yana jihadin ne don kansa. Lalle Allah tabbas Mawadaci ne daga talikai.

7. Waɗanda kuma suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, tabbas za Mu kankare musu munanan ayyukansu, kuma tabbas za Mu saka musu mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk wanda ya yi imani da ranar lahira yake fatan haɗuwa da Allah a wannan rana domin ya yi masa kyakkyawan sakamako bisa kyawawan ayyukansa, to ya sani Allah ba zai tozarta masa aikinsa ba, kuma lokacin da ya ajiye na zuwan wannan rana yana nan tafe ba da jimawa ba. Allah ya tabbatar da cewa shi mai jin maganganun bayinsa ne kuma masanin ayyukansu, ba abin da zai kuɓuce masa daga ciki kuma zai yi musu sakayya a kai.
Sai kuma Allah ya bayyana cewa abin da ya ɗora wa bayinsa na ayyuka ba don amfaninsa ba ne sai don amfanin kansu, don haka duk wanda ya yaƙi zuciyarsa ya yi wa Allah ɗa'a, ya kuma guje wa saɓa masa, to ya sani ya yi ne don kansa, domin kuwa shi zai ci moriyar aikinsa, Allah ba ya buƙatar komai daga halittunsa; biyayyarsu ba za ta ƙare shi da komai ba, hakanan saɓawarsu ba za ta rage shi da wani abu ba.
Sannan ya bayyana yalwar rahamarsa da kyautatawarsa ga halittunsa duk kuwa da kasancewarsa ba ya amfana daga gare su da komai, ya kuma tabbatar da cewa bayinsa waɗanda suka yi imani suka yi haƙuri a kan jarrabawarsa gare su suka kuma yi ayyuka nagari, to lalle zai shafe musu zunubbansu kuma a lahira zai yi musu sakayya fiye da abin da suka kasance suna aikatawa a duniya, domin zai riɓanya musu ladan ayyukansu tun daga ninki goma har zuwa ninki ɗari bakwai, zuwa adadi ba iyaka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin biyayya ga iyaye ko da ba Musulmi ne ba, da kyautata musu a magana da aiki, da haramcin saɓa musu.

2. Haramcin yin biyayya ga iyaye a kan abin da ya saɓa wa Allah.

3. Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama da komawar kowa ga Allah da hisabi da sakamako.

4. Duk wani mutum mumini nagari to Allah zai tashe shi ranar alƙiyama tare da ‘yan’uwansa mutanen kirki don ya yi masa sakayya irin tasu.

5. Imani ba ya inganta sai an haɗa shi da ayyuka na ƙwarai.

Suratul Ankabut (8-9)
وَوَصَّيۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيۡهِ حُسۡنٗاۖ وَإِن جَٰهَدَاكَ لِتُشۡرِكَ بِي مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٞ فَلَا تُطِعۡهُمَآۚ إِلَيَّ مَرۡجِعُكُمۡ فَأُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٨
وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُدۡخِلَنَّهُمۡ فِي ٱلصَّٰلِحِينَ ٩

8. Kuma Mun yi wa mutum wasiyya da kyautata wa iyayensa; idan kuma suka yaƙe ka kan ka yi shirka da Ni game da abin da ba ka da sani a kansa, to kada ka bi su. Wurina ne makomarku take kawai, sannan zan ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa.

9. Waɗanda kuma suka yi imani suka yi ayyuka nagari tabbas za Mu shigar da su cikin salihai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan’adam wasiyyar kyautata wa iyayensa da suka haife shi, lallai ya yi musu magana mai daɗi kuma ya kyautata musu a aikace. To amma yayin da za su matsa masa a kan sai ya haɗa Allah da wani abu wajen bauta wanda ba shi da wani ilimi ko wata hujja a kansa, to kada ya yi musu biyayya a kan haka, domin babu biyayya ga wani mahaluƙi a kan saɓa wa mahalicci.

An karɓo daga Sa’ad ɗan Abi Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Mahaifiyata ta ce mini: “Ba zan ƙara cin abinci ko in sha abin sha ba har sai ka kafirce wa Muhammad.” Sai ta daina cin komai ta daina shan komai har sai da ta kai sai sun buɗe bakinta da sanda sun ɗura mata abinci ko abin sha. Sai wannan ayar ta sauka.” [Ahmad #1614].

Sai kuma Allah ya bayyana cewa makomar kowa zuwa gare shi ne shi kaɗai, watau ranar alƙiyama sannan zai ba kowa labarin abin da ya aikata a nan duniya kuma zai saka masa gwargwadon aikinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka yi imani da shi suka kuma yi ayyuka nagari, da cewa zai shigar da su cikin mutanen ƙwarai a ranar alƙiyama, ya tashe su tare, ya ba su lada irin nasu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani na gaskiya yana sanya mai shi juriya da haƙuri a kan cutarwar kafirai.

2. Bayanin kafircin munafukai ko da kuwa suna da’awar sun yi imani.

3. Bayanin cewa munafukai sun bayyana imaninsu ne da farko domin abin da suke tsammanin samu na maslaharsu yayin da Musulmi suka yi nasara a kan kafirai.

Suratul Ankabut (10-11)

وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَقُولُ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ فَإِذَآ أُوذِىَ فِى ٱللَّهِ جَعَلَ فِتْنَةَ ٱلنَّاسِ كَعَذَابِ ٱللَّهِ ۖ وَلَئِن جَآءَ نَصْرٌ مِّن رَّبِّكَ لَيَقُولُنَّ إِنَّا كُنَّا مَعَكُمْ ۚ أَوَ لَيْسَ ٱللَّهُ بِأَعْلَمَ بِمَا فِى صُدُورِ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٠﴾ وَلَيَعْلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَلَيَعْلَمَنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ ﴿١١﴾

10. Kuma cikin mutane akwai mai cewa: “Mun yi imani da Allah,” to idan aka cuce shi a kan hanyar Allah sai yakan ɗauki fitinar mutane kamar azabar Allah, lalle kuwa idan wata nasara ta zo daga Ubangijinka, tabbas zai riƙa cewa: “Lalle mu mun kasance tare da ku.” Yanzu Allah ba Shi Ya fi kowa sanin abin da ke cikin zukatan talikai ba?

11. Tabbas kuma Allah zai bayyana waɗanda suka yi imani, kuma tabbas zai bayyana munafukai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ɓangare na siffofin munafukai masu yin imani da fatar baki kawai amma zukatansu ba su rabu da kafirci ba. Allah ya nuna cewa munafuki zai yi ta cika baki da faɗar ya yi imani, to amma idan wata jarraba ta same shi ta tsangwama da cutarwa daga kafirai sai ya kasa jurewa, har ma ya ɗauki azabar kafirai a gare shi kamar azabar Allah, sai kawai ya yi ridda ya koma ga kafirci. To amma yayin da nasarar Ubangiji ta zo wa Manzonsa da muminai suka samu galaba a kan kafirai, sai ya dawo yana tabbatar wa muminai cewa shi ma yana tare da su, yana nan da imaninsa bai yi ridda ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗakar da shi cewa, shin ya manta ne Allah yana sane da duk abin da mutane suke ɓoyewa a zukatansu? Tabbas babu abin da yake ɓuya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) na kafirci ko na imani, to ta yaya za su ce su za su ba wa Allah labarin abin da yake zukatansu bayan ya fi su sanin komai?
Sai Allah ya tabbatar da cewa lalle sai ya jarraba mutane ta kowace fuska, abu mai daɗi da marar daɗi domin ya bambance tsakanin muminai na gaskiya da kuma maƙaryata munafukai, ya kuma saka wa kowa daidai da aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Musulunci yana tabbatar da cewa kowa shi kaɗai zai ɗauki nauyin zunubinsa, babu mai iya ɗauke masa ko ya taya shi ɗauka. Ko da a ce wani ya bugi ƙirjin cewa zai ɗauke wa wani zunubinsa, to ƙarya yake masa, domin wannan haƙƙin ba nasa ne ba na Allah ne, babu kuma wanda Allah ya ba shi hurumin yin wani tasarrufi cikin haƙƙinsa ba da izininsa ba ko umarninsa.

2. Duk wanda ya ɗora wani a kan hanyar ɓata, to lalle sai ya ɗauki nauyin wannan zunubin ɓatarwar ranar gobe alƙiyama ba tare da an rage wa waɗanda suka bi shi a kan ɓatansa wani abu na zunubansu ba.

3. Maganar kafirai ta cewa a bi su a kan kafircinsu su za su ɗauke wa duk wanda ya bi su nauyin zunubansa izgili ne suke yi wa Musulmi, domin ba su ma yi imani da ranar alƙiyama ba balle su yarda da cewa akwai wani sakamako da yake jiran su, suna dai faɗar irin waɗannan maganganu ne don baƙanta wa muminai rai da yaudarar wawayen cikinsu.

Suratul Ankabut (12-13)

وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱتَّبِعُوا۟ سَبِيلَنَا وَلْنَحْمِلْ خَطَٰيَٰكُمْ وَمَا هُم بِحَٰمِلِينَ مِنْ خَطَٰيَٰهُم مِّن شَىْءٍ ۖ إِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ﴿١٢﴾ وَلَيَحْمِلُنَّ أَثْقَالَهُمْ وَأَثْقَالًا مَّعَ أَثْقَالِهِمْ ۖ وَلَيُسْـَٔلُنَّ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ عَمَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿١٣﴾

12. Kuma waɗanda suka kafirta suka ce da waɗanda suka yi imani: “Ku bi tafarkinmu, (mu) lalle za mu ɗauke muku kurakuranku,” alhali kuwa su ba za su iya ɗauke wani abu na kurakuransu ba; lalle su dai tabbas maƙaryata ne.

13. Tabbas kuma za su ɗauki zunubansu da kuma wasu zunuban tare da zunubansu; kuma tabbas za a tambaye su a ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna ƙirƙira.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kafiran Kuraishawa suna zolayar muminai da cewa su zo su bi addininsu su ci gaba da ayyuka irin nasu, idan an je lahira wai su za su ɗauke musu zunubansu, don haka idan an zo yin uƙuba su za a yi wa ba muminai da suka bi su ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani ya tabbatar da ƙaryarsu da cewa ba za su ɗauke wa muminai wani abu na zunubansu ba idan har suka kuskura suka bi su, domin kuma tabbas su kafirai maƙaryata ne.
Sai kuma Allah ya tabbatar da cewa su waɗannan kafirai masu ƙoƙarin su yi wa Musulmi shigo-shigo-ba-zurfi ba zai ƙyale su hakanan ba tare da ya ƙara musu wani nauyin zunubi a kan nasu na da ba. Ya tabbatar musu cewa lalle sai sun ɗauki nauyin zunubansu waɗanda suka aikata tare da zunuban waɗanda suka bi kiraye-kirayensu na kafirci, ba kuma tare da sun rage wa mabiyansu wani abu daga cikin zunubansu ba. Ya ƙara tabbatar musu cewa ranar alƙiyama lallai sai an tambaye su game da ƙarairayin da suka riƙa ƙirƙira a duniya.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk wanda ya yi kira zuwa ga shiriya, to yana da lada kwatankwacin ladan waɗanda suka bi shi, kuma wannan ba zai tauye wani abu na ladansu ba. Duk kuma wanda ya yi kira zuwa ga ɓata, to yana da zunubi kwatankwacin zunuban waɗanda suka bi shi, kuma wannan ba zai rage wani abu daga zunubansu ba.” [Muslim #2674].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana lallashin Annabi (ﷺ) game da tsangwamar kafirai da cutarwarsu gare shi da muminai da kuma bijire wa kiransa zuwa ga Allah. Ya nuna masa cewa ya duba ya ga Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da tsawon lokacin da ya ɗauka yana wa’azi ga mutanensa da irin cutarwarsu gare shi da ƙaryata shi da suka yi, amma Allah ya saurara musu tsawon lokaci, shi kuma Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi ta haƙuri da su, daga ƙarshe Allah ya hallaka su ya tserar da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa. Wannan kaɗai ya isa wa’azi ga Manzo (ﷺ) da kwantar masa da hankali, domin shi bai yi daɗewar da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi ba, sannan kuma ya samu magoya baya muminai masu ɗimbin yawa waɗanda Annabi Nuhu bai samu kamarsu ba.

2. Karfafa gwiwa ga duk wani mai kira zuwa ga Allah a kan cewa, kada ya sare ko ya fitar da ƙauna, don ganin ya ɗauki lokaci mai tsawo yana kira amma ba a samu masu amsa kiransa sosai ba. Ya tuna jajircewar Annabi Nuhu ya kuma fahimci cewa shiriya a hannun Allah take shi kaɗai, yana shiryar da wanda ya ga dama, ya kuma ɓatar da wanda ya ga dama.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya jirgin ruwa na Annabi Nuhu ya zama aya ga talikai, su ɗau izina a kan cewa, duk wanda ya ƙaryata manzannin Allah to ƙarshensa hallaka ce. Muminai kuma su fahimci cewa, duk wata damuwa Allah zai yaye ta, duk wani ƙunci zai kawo masa mafita. Sannan Allah ya sanya jinsin jirgin ruwa ya zama aya ga mutane domin su gane ni’imar Allah gare su, da ya hore musu hanyoyin ƙera shi, don su hau kansa su ɗora kayayyakinsu masu nauyi daga ƙasa zuwa ƙasa.

Suratul Ankabut (14-15)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ فَلَبِثَ فِيهِمۡ أَلۡفَ سَنَةٍ إِلَّا خَمۡسِينَ عَامٗا فَأَخَذَهُمُ ٱلطُّوفَانُ وَهُمۡ ظَٰلِمُونَ ١٤ فَأَنجَيۡنَٰهُ وَأَصۡحَٰبَ ٱلسَّفِينَةِ وَجَعَلۡنَٰهَآ ءَايَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ ١٥

14. Kuma haƙiƙa Mun aiko Nuhu zuwa ga mutanensa, sai ya zauna cikinsu shekara dubu ba hamsin, sai (ruwan) Ɗufana ya ci su, alhalin suna azzalumai.

15. Sai Muka tserar da shi tare da mutanen jirgin ruwa, Muka kuma sanya shi (jirgin) aya ga talikai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wani ɓangare na ƙissar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda shi ne farkon manzannin Allah. Ya bayyana cewa ya aiko shi zuwa ga mutanensa masu shirka da Allah domin ya kirawo su zuwa ga kaɗaita Allah; ya zauna a cikinsu yana yi musu wa'azi yana kiran su zuwa kaɗaita Allah da bauta har tsawon shekara ɗari tara da hamsin, amma sai suka ƙaryata shi suka doge a kan kafircinsu da shirkarsu; mutane ƙalilan ne suka yi imani da shi. Sai ya roƙi Allah ya aiko musu da ruwan Ɗufana don ya hallaka su suna kan zaluncinsu da kafircinsu ba su bari ba.
Allah kuma ya bayyana cewa ya karɓi roƙonsa ya hallaka kafirai gaba ɗaya kuma ya kubutar da Annabi Nuhu da muminan da suke tare da shi a cikin jirgin ruwa daga hallakar nutsewa cikin ruwa, ya kuma bar wannan jirgin ruwa don ya zama abin izina ga mutane.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Da'awar annabawa ta farko ita ce kira zuwa ga kaɗaita Allah da bauta da watsi da duk wani abin bauta ba shi ba.

2. Bauta wa Allah da kiyaye dokokinsa shi ne alheri ga mutane, domin ita ce hanya ɗaya tilo ta samun ɗaukaka da mutunci a duniya da lahira. Duk wani alheri da aka samu a duniya da lahira to bautar Allah da tsoron sa ne suka haifar da shi.

3. Duk abin da yinsa aka yi ba shi ne ya yi kansa ba, sannan bai mallaki amfanarwa da cutarwa a hannunsa ba; ba ya arzutawa ko ya talauta, to wannan ko kusa bai cancanci a bauta masa ba, domin tauyayye ne kuma gajiyayye.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da a nemi arziki a wurinsa. Wannan ya nuna cewa dole ne mutum ya tashi ya nema, ba zai shantake wuri guda ba ya ce arzikinsa zai zo ya same shi, dole ne ya yi riƙo da sababi sannan ya dogara ga Allah ya nema a wurinsa.

5. Isar da saƙo shi ne aikin da Allah ya ɗora wa manzanninsa. Amma sadar da shiriya zuwa zukata wannan aikin Allah ne shi kaɗai.

Suratul Ankabut (16-18)

وَإِبۡرَٰهِيمَ إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُۖ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ١٦ إِنَّمَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوۡثَٰنٗا وَتَخۡلُقُونَ إِفۡكًاۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَا يَمۡلِكُونَ لَكُمۡ رِزۡقٗا فَٱبۡتَغُواْ عِندَ ٱللَّهِ ٱلرِّزۡقَ وَٱعۡبُدُوهُ وَٱشۡكُرُواْ لَهُۥٓۖ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ١٧ وَإِن تُكَذِّبُواْ فَقَدۡ كَذَّبَ أُمَمٞ مِّن قَبۡلِكُمۡۖ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ١٨

16. Kuma (ka tuna) Ibrahimu lokacin da ya ce da mutanensa: “Ku bauta wa Allah, kuma ku kiyaye dokokinsa, wannan shi ya fi muku alheri in kun kasance kun san (haka).

17. Lalle abin da kuke bauta wa ba Allah ba gumaka ne kawai, kuna kuma ƙirƙirar ƙarya ne. Lalle waɗanda kuke bauta wa ba Allah ba, ba su mallaki wani arziki ba gare ku , sai ku nemi arziki a wurin Allah, kuma ku bauta masa, ku kuma gode masa; gare Shi ne kawai za a mayar da ku.

18. Idan kuma kuka ƙaryata, to haƙiƙa da ma wasu al’ummun da suke gabaninku sun ƙaryata; ba abin da yake kan Manzo sai isar da saƙo mabayyani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya aika manzonsa Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga mutanensa don ya kirawo su zuwa ga kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sai ya umarce su da su ji tsoron Allah su kiyaye dokokinsa ta hanyar aikata umarninsa da guje wa haninsa. Yin haka ya fi musu alheri in sun kasance sun san haka.
Sannan ya nuna musu kyawun abin da yake kiran su a kansa da kuma munin abin da suke a kai na yin shirka da Allah. Abin da suke bauta wa ba komai ba ne face gumaka waɗanda ba za su amfane su da komai ba, ba kuma za su kare su daga wata cuta ba. Ya tabbatar musu da cewa ƙarya ce kawai suke ƙirƙira da kansu, domin su ne suke sassaƙa su da hannayensu suke kuma sanya musu sunaye sannan daga bisani su riƙa bauta musu. Allah kuma ya sake jan hankalinsu a kan su lura cewa waɗannan gumakan nasu ba su cancanci bauta ba, domin ba su mallaki komai na arziki da za su arzuta su da shi ba. Sai su nemi arziki a wurin Allah domin shi kaɗai ne mai arzutawa, su kuma bauta masa shi kaɗai, su gode masa bisa ni’imar arziki iri-iri da ya yi musu, kuma su sani gare shi kaɗai za su koma a ranar alƙiyama don ya yi musu hisabi da sakamako a kan ayyukansu. Gumakansu kuma ba su da wani abu daga cikin waɗannan.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunanar da mushirikai cewa idan sun ƙaryata abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da shi, to ba su ne farau ba a kan haka, akwai al’ummu da dama da suka gabace su, kamar mutanen Annabi Nuhu da Adawa da Samudawa, dukkansu sun ƙaryata manzanninsu, Allah kuma ya hallaka su. Shi kuma Manzo babu abin da yake kansa sai isar da saƙo a sarari, wanda ya gaskata ya tsira, wanda kuwa ya ƙaryata to don kansa. Shi kam Manzon Allah ya isar musu da duk abin da Allah ya umarce shi ya isar gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jawo hankalin kafirai masu ƙaryata tashin halittu bayan mutuwa ta hanyar nuna musu dalilai na hankali da duk wanda ya yi amfani da hankalin da Allah ya ba shi zai gane gaskiyar abin da ake faɗa masa.

2. Tabbatar da aƙidar tashi bayan mutuwa da sakamakon ayyuka.

3. Tabbatar wa da ɗan’adam cewa ba zai guje wa Allah ba duk inda ya je yana ƙarƙashin ikonsa. Wannan kaɗai ya isa ya sanya shi ya koma zuwa ga Allah da yin imani da taƙawa tun a nan duniya kafin a je lahira.

4. Tabbatar da cewa kafiri ba zai shiga Aljanna ba har abada, makomarsa wutar Jahannama ce.

5. Ba ya halatta ga mumini ya ɗebe ƙauna daga samun rahamar Allah.

Suratul Ankabut (19-23)

أَوَ لَمۡ يَرَوۡاْ كَيۡفَ يُبۡدِئُ ٱللَّهُ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥٓۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ١٩ قُلۡ سِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ بَدَأَ ٱلۡخَلۡقَۚ ثُمَّ ٱللَّهُ يُنشِئُ ٱلنَّشۡأَةَ ٱلۡأٓخِرَةَۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٠ يُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ وَيَرۡحَمُ مَن يَشَآءُۖ وَإِلَيۡهِ تُقۡلَبُونَ ٢١ وَمَآ أَنتُم بِمُعۡجِزِينَ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِي ٱلسَّمَآءِۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٖ ٢٢ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَلِقَآئِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ يَئِسُواْ مِن رَّحۡمَتِي وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٢٣

19. Yanzu ba su ga yadda Allah Yake farar halitta ba, sannan Shi ne kuma zai mayar da ita? Lalle wannan mai sauƙi ne a wurin Allah.

20. Ka ce: “Ku yi tafiya a bayan ƙasa sai ku duba ku ga yadda Allah Ya fari halittu. Sannan Allah ne zai sake samar da su samarwar ƙarshe. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai.

21. “Yana azabtar da wanda Ya ga dama, Yana kuma jin ƙan wanda Ya ga dama; kuma wurinsa kawai za a mayar da ku.

22. “Kuma ku ba za ku gagara ba a ƙasa ko kuma a sama; kuma ba ku da wani majiɓinci ko mataimaki in ba Allah ba.”

23. Waɗanda kuma suka kafirce wa ayoyin Allah da kuma gamuwa da Shi, waɗannan sun ɗebe ƙauna daga rahamata, kuma waɗannan suna da azaba mai raɗaɗi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya juyo a kan kafiran Makka waɗanda suke ƙaryata tashi bayan mutuwa da hisabi ranar alƙiyama, ya bayyana musu cewa ba su ga yadda Allah ya fari halitta ba daga babu? Sannan kuma shi ne zai sake dawo da ita bayan gushewarta, wannan kuma abu ne mai sauƙi ƙwarai a gunsa don babu abin da yake gagarar sa.
Sannan ya umarci Manzon Allah (ﷺ) ya umarci waɗannan mushirikan su yi tafiya a bayan ƙasa su duba su ga yadda Allah ya fari halittar mutane da dabbobi da tsirrai da itatuwa, sannan da yadda suke mutuwa kaɗan-kaɗan. Kuma shi ne wanda zai sake raya su a karo na biyu bayan mutuwarsu don yi musu hisabi da sakamakon ayyukansu masu kyau da marasa kyau. Lalle Allah mai iko ne a kan komai babu abin da zai gagare shi, watau kamar yadda fara halittarsu ba ta gagare shi ba, to hakanan sake tashinsu bayan mutuwarsu ba zai gagare shi ba.
Sai kum Allah ya bayyana adalcinsa da falalarsa a ranar alƙiyama inda zai azabtar da wanda ya ga dama da adalcinsa, ya kuma ji ƙan wanda ya ga dama da falalarsa, kuma wajensa ne shi kaɗai za a mayar da su a ranar alƙiyama domin hisabi a kan ayyukansu.
Kuma su waɗannan kafirai masu ƙaryata tashi bayan mutuwa da zuwan ranar alƙiyama su sani ba za su iya gagarar Allah ba har su tsere masa a sama ko a ƙasa, duk inda za su shiga suna cikin damƙarsa. Ya kuma tabbatar musu cewa babu wani wanda ya isa ya taimaka musu ya kare su daga azabar Allah a sama ko a ƙasa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin da kafirai masu ƙaryata zuwan lahira da cewa su ne waɗanda suka kafirce wa ayoyin Allah da haɗuwa da shi a ranar alƙiyama, to waɗannan su ne waɗanda suke ɗebe ƙauna daga samun rahamar Allah, domin ba su yi wani aiki mai kyau da zai sa su yi tsammanin samunta ba, don haka har abada ba su ba shiga Aljanna saboda kafircinsu. Waɗannan suna da azaba mai raɗaɗi tana jiran su a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk lokacin da masu faɗa da gaskiya suka kasa tunkarar ta da hujja sai su koma ga amfani da ƙarfi da barazanar kisa domin murƙushe mai gaskiya.

2. Allah yakan jiɓinci kula da bayinsa nagari ya tserar da su daga makircin maƙiyansu.

3. Duk waɗanda suka bauta wa wasu abubuwa ba Allah ba, to a ranar alƙiyama ababen bautarsu za su yi baram-baram da su, su rabu suna la'antar juna.

4. Mutanen Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun haɗu sun zuga juna domin taimakon gumakansu, saboda suna zaton da haka ne su ma za su samu taimakon su ranar alƙiyama, sai Allah ya nuna musu abin sam ba haka yake ba; hasali ma a ranar ba za su sami wani taimako ba daga duk abubuwan da suka bauta wa ba Allah ba, sai ma su zama ababen gabarsu.

5. Falalar yin hijira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Bayan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bar mutanensa ya yi hijira Allah bai faɗa mana cewa ya hallaka su bayan tafiyarsa ba. Abin da ake faɗa a wasu labarai marasa tushe na cewa Allah ya hallaka su da sauro wanda ya riƙa shan jininsu, wannan ba gaskiya ba ne, domin da haka ya faru da Allah ya ambace shi a cikin Alƙur'ani kamar yadda ya ambaci yadda ya hallakar da sauran al'ummu da suka ƙaryata annabawansu. Watakila Allah ya ƙyale su ne domin Annabi Ibrahimu bai yi musu wata mummunar addu'a ba ko ya roƙi Allah ya hallaka su. Allah ya siffanta shi a wurare daban-daban da cewa shi mutum ne mai haƙuri da juriya, kuma mai tausayi. Dubi yadda tausayinsa ya sanya shi yin jayayya da mala'ikun da aka aiko domin su hallaka mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) saboda kafircinsu, duk kuwa da cewa ba mutanensa ba ne.

7. Allah ya sanya annabta a cikin zurriyyar Annabi Ibrahimu; duk wani annabi da ya zo a bayansa to daga cikin zurriyyarsa ne. Hakanan ba wanda aka saukar wa da wani littafi sai a cikinsu har sanda Allah ya aiko da na ƙarshensu Annabi Muhammad (ﷺ).

Suratul Ankabut (24-27)

فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُواْ ٱقْتُلُوهُ أَوْ حَرِّقُوهُ فَأَنجَىٰهُ ٱللَّهُ مِنَ ٱلنَّارِۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٢٤﴾ وَقَالَ إِنَّمَا ٱتَّخَذْتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ أَوْثَٰنًا مَّوَدَّةَ بَيْنِكُمْ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَاۖ ثُمَّ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يَكْفُرُ بَعْضُكُم بِبَعْضٍ وَيَلْعَنُ بَعْضُكُم بَعْضًا وَمَأْوَىٰكُمُ ٱلنَّارُ وَمَا لَكُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿٢٥﴾ ۞فَامَنَ لَهُۥ لُوطٌ وَقَالَ إِنِّى مُهَاجِرٌ إِلَىٰ رَبِّىٓۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٢٦﴾ وَوَهَبْنَا لَهُۥٓ إِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَجَعَلْنَا فِى ذُرِّيَّتِهِ ٱلنُّبُوَّةَ وَٱلْكِتَٰبَ وَءَاتَيْنَٰهُ أَجْرَهُۥ فِى ٱلدُّنْيَاۖ وَإِنَّهُۥ فِى ٱلْءَاخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ﴿٢٧﴾

24. To ba wani jawabi da ya fito daga bakin mutanensa sai cewa da suka yi: "Ku kashe shi ko kuma ku ƙone shi!" Sai Allah Ya tserar da shi daga wutar. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suka yi imani.

25. Kuma ya ce (da su): "Lalle ba abin da kuka riƙa wanin Allah sai gumaka kawai don ƙauna da take tsakaninku a rayuwar duniya; sannan ranar alƙiyama wasunku za su kafirce wa wasu, kuma wasunku za su la'anci wasu, makomarku kuma wuta ce, ba ku da kuwa wasu mataimaka."

26. Sai Luɗu ya yi imani da shi. (Sai Ibrahimu) kuma ya ce: “Lalle ni mai yin hijira ne zuwa ga Ubangijina; lalle Shi Mabuwayi ne, Mai hikima.”

27. Muka kuma yi masa baiwa da (ɗansa) Is’haƙa da kuma (jikansa) Ya'aƙubu, Muka kuma sanya annabta da littafi a cikin zuriyarsa, Muka kuma ba shi ladansa a duniya; kuma lalle shi a lahira tabbas yana cikin salihai.

Waɗannan ayoyi ci gaba ne da labarin Annabi Ibrahimu da mutanensa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kira mutanensa zuwa ga kaɗaita Allah da bauta da watsi da bautar wanin Allah cikin hikima da ilimi, amma sai mutanensa suka mayar masa da mummunan martani ta hanyar umartar junansu da cewa su kashe Annabi Ibrahimu ko ma su jefa shi cikin wuta ya ƙone ƙurmus domin su taimaka wa gumakansu. Haka kuwa suka yi suka jefa shi wuta, amma sai Allah ya kuɓutar da shi. Allah kuma ya tabbatar da cewa lalle a game da abin da ya faru na jefa Annabi Ibrahimu cikin wuta da kuɓutar da shi ba shakka akwai ayoyi masu ɗauke da izina da darussa ga muminai, domin su ne masu ɗaukar izina daga abin da manzanni suka zo da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu nasihohin da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya riƙa yi wa mutanensa da cewa, sun riƙi gumaka ne suna bauta musu ba Allah ba domin kawai su ƙarfafa soyayyar da ke tsakaninsu da junansu a nan duniya, to amma su sani cewa a lahira wannan soyayyar za ta yanke, za su yi baram-baram da junansu lokacin da za su ga azaba ƙuru-ƙuru, su yi ta tsine wa junansu, daga ƙarshe matabbatarsu ita ce wutar Jahannama, ba su da kuwa wasu mataimaka da za su kare su daga aukawa cikin azabar Allah; gumakansu ba za su tsinana musu komai ba a wannan rana.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da da’awarsa yana ta kiran mutanensa zuwa ga Tauhidi har lokacin da ɗan’uwansa Annabi Luɗu ya yi imani da shi, mutanensa kuma suka bijire wa kiransa, wa’azinsa bai amfane su da komai ba, daga nan sai ya yanke shawarar yin hijira zuwa ƙasar Sham mai albarka don ya ci gaba da bautar Ubangijinsa a can domin Allah shi ne mabuwayi, babu mai iya rinjayar sa, kuma duk wanda ya yi hijira zuwa gare shi ba zai ƙasƙanta ba, kuma mai hikima ne cikin duk abin da ya ƙaddara ya kuma tsara.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan Annabi Ibrahimu ya yi hijira zuwa Sham sai ya yi masa kyautar Is’haƙa da ɗansa Ya’aƙub, ya kuma ƙara yi masa wata baiwar mai girma ta sanya annabta a cikin ‘ya’yansa ya saukar musu da littattafai, ya kuma ba shi ladan haƙuri da juriyar da ya yi a kan gaskiya a nan duniya, ya gyara masa ‘ya’yansa ya sanya masa kyakkyawan ambato cikin mutane, sannan kuma lalle a lahira za a yi masa sakamako irin wanda ake yi wa mutanen kirki; abin da aka ba shi a nan duniya kuma ba zai sa a rage masa abin da zai samu a lahira ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutanen Annabi Luɗu ne farkon waɗanda suka fara mummunar al’adar neman maza da lalata.

2. Neman maza wata ɗabi’a ce da duk wani mai hankali zai iya riskar muninta.

3. Fitowa bainar jama’a ana aikata ayyukan baɗala da rashin kunya mummunan abu ne.

4. Aikin mutanen Annabi Luɗu shi ne yaɗa ɓarna a bayan ƙasa.

Suratul Ankabut (28-30)

وَلُوطًا إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ إِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلْفَٰحِشَةَ مَا سَبَقَكُم بِهَا مِنْ أَحَدٍ مِّنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٨﴾ أَئِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلرِّجَالَ وَتَقْطَعُونَ ٱلسَّبِيلَ وَتَأْتُونَ فِى نَادِيكُمُ ٱلْمُنكَرَ ۖ فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوا۟ ٱئْتِنَا بِعَذَابِ ٱللَّهِ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٢٩﴾ قَالَ رَبِّ ٱنصُرْنِى عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٣٠﴾

28. Kuma (ka tuna) Luɗu lokacin da ya ce da mutanensa: “Lalle ku kuna zaike wa mummunan aiki wanda ba wani mutum guda daga talikai da ya rigaye ku (aikata) shi.

29. “Yanzu kwa riƙa zaike wa maza, ku kuma riƙa tsare hanya (kuna yin fashi), kuma kuna aikata abin ƙi a cikin majalisarku?” Ba wani jawabi da ya fito daga bakin mutanensa sai cewa suka yi: “To ka zo mana da azabar Allah idan ka kasance cikin masu gaskiya.”

30. (Sai Luɗu) ya ce: “Ya Ubangijina, Ka taimake ni kan mutanen nan maɓarnata.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya aiko da Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga mutanen Sadum waɗanda suka shahara da wata mummunar al’ada ta neman maza domin biyan buƙatar sha’awarsu. Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gargaɗe su a kan wannan mummunan aiki da suke yi wanda ba a taɓa samun wasu suna aikata irinsa ba gabaninsu; su ne farkon waɗanda suka tsiri wannan mummunan laifi wanda duk wani mai lafiyayyen hankali zai ƙyamace shi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mutanensa kashedi game da munanan ayyukan da suke yi, inda suka riƙa biyan buƙatar sha’awarsu da maza, sannan su riƙa tsare hanya suna yi wa matafiya fashi, mutane kuma suna jin tsoron bin hanyoyinsu domin gudun su tsare su su yi lalata da su. Sannan suna aikata miyagun ayyuka a majalisunsu, kamar nuna tsiraici da cutar da masu wucewa a hanya da maganganunsu ko da ayyukansu.
Sai Allah ya nuna cewa a maimakon su karɓi nasihar da Annabi Luɗu ya yi musu sai ya zamanto babu abin da ya fito daga bakinsu sai cewa suka yi ya sauko musu azabar Allah da yake razana su da ita, idan har abin da yake faɗa musu gaskiya ne.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ganin irin yadda mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka nuna taurin kansu da neman ya saukar musu da azaba, sai ya roƙi Allah ya taimake shi a kan waɗannan mutane maɓarnata masu yaɗa kafirci da fitsara a bainar jama’a.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin tausayawar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga Annabi Ibrahimu da ya gabatar masa da albishir na samun haihuwa kafin ya ba shi labarin niyyar hallakar da mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), saboda Allah ya san cewa Annabi Ibrahimu mutum ne mai tausayi matuƙa da haƙuri.

2. Aikata alfasha da saɓon Allah zalunci ne da ke jawo fushin Allah.

3. Annabawa sukan ji tsoro na ɗabi’a, wanda hakan ba tawaya ba ce.

4. Kula da baƙi da jiye musu tsoron abin da zai cutar da su.

5. Masu hankali su ne suke ɗaukar izina daga ayoyin Allah.

Suratul Ankabut (31-35)

وَلَمَّا جَآءَتۡ رُسُلُنَآ إِبۡرَٰهِيمَ بِٱلۡبُشۡرَىٰ قَالُوٓاْ إِنَّا مُهۡلِكُوٓاْ أَهۡلِ هَٰذِهِ ٱلۡقَرۡيَةِۖ إِنَّ أَهۡلَهَا كَانُواْ ظَٰلِمِينَ ٣١ قَالَ إِنَّ فِيهَا لُوطٗاۚ قَالُواْ نَحۡنُ أَعۡلَمُ بِمَن فِيهَاۖ لَنُنَجِّيَنَّهُۥ وَأَهۡلَهُۥٓ إِلَّا ٱمۡرَأَتَهُۥ كَانَتۡ مِنَ ٱلۡغَٰبِرِينَ ٣٢ وَلَمَّآ أَن جَآءَتۡ رُسُلُنَا لُوطٗا سِيٓءَ بِهِمۡ وَضَاقَ بِهِمۡ ذَرۡعٗاۖ وَقَالُواْ لَا تَخَفۡ وَلَا تَحۡزَنۡ إِنَّا مُنَجُّوكَ وَأَهۡلَكَ إِلَّا ٱمۡرَأَتَكَ كَانَتۡ مِنَ ٱلۡغَٰبِرِينَ ٣٣ إِنَّا مُنزِلُونَ عَلَىٰٓ أَهۡلِ هَٰذِهِ ٱلۡقَرۡيَةِ رِجۡزَۢا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُواْ يَفۡسُقُونَ ٣٤ وَلَقَد تَّرَكۡنَا مِنۡهَآ ءَايَةَۢ بَيِّنَةٗ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ٣٥

31. Lokacin kuwa da manzanninmu suka zo wa Ibarahimu da albishir, sai suka ce: “Lalle mu masu hallaka mutanen wannan alƙaryar ne, lalle mutanenta sun kasance azzalumai.”

32. Sai (Ibrahimu) ya ce: “Lalle Luɗu yana cikinta”. Sai suka ce: “Mu muka fi sanin waɗanda suke cikinta; tabbas za mu tserar da shi tare da iyalinsa, sai matarsa kawai da ta kasance cikin waɗanda za su yi saura (a hallaka su tare)”.

33. Lokacin kuma da manzanninmu suka zo wa Luɗu, sai ya yi baƙin ciki da zuwansu, zuciyarsa kuma ta ƙuntata saboda su, sai suka ce da shi: “Kada ka ji tsoro, kuma kada ka damu; lalle mu masu tserar da kai ne tare da iyalinka, sai matarka kawai da ta kasance cikin waɗanda za su yi saura (a hallaka su tare).

34. “Lalle mu masu saukar da azaba ce daga sama a kan mutanen wannan alƙaryar saboda abin da suka kasance suna aikatawa na fasiƙanci.”

35. Kuma haƙiƙa Mu mun bar aya bayyananniya game da ita (alƙaryar) ga mutanen da suke hankalta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya karɓi addu’ar Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya aiko da mala’iku domin hallaka mutanensa. Sai mala’ikun nan suka fara biyawa ta wajen Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don su yi masa albishir da samun haihuwar ɗansa Is’haƙa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kuma jikansa Ya’aƙub (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sai Annabi Ibrahim ya so ya san inda suka nufa daga wajensa, sai suka bayyana masa cewa za su je ne su hallaka mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) domin sun tabbata mutane ne azzalumai saboda aikata alfasha da suke yi. Daga nan sai Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga tattaunawa da su a kan haka, ya nuna musu a wannan alƙarya da za su hallakar akwai Annabi Luɗu wanda shi ba azzalumi ne irinsu ba. Sai mala’ikun suka amsa masa da cewa su ne suka fi shi sanin waɗanda suke cikin wannan alƙarya ta Sadum, suka kuma tabbatar masa da cewa lalle za su tserar da Annabi Luɗu da iyalansa daga wannan azabar in ban da matarsa, ita kam tana cikin waɗanda za a hallakar.

Sai mala’ikun suka nufi alƙaryar mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da isarsu gidansa aka kuma sanar da shi ya yi baƙi, sai ya yi baƙin ciki da zuwansu, ya shiga matsananciyar damuwa domin jiye musu tsoron mugun halin mutanensa, musamman saboda mala’ikun sun zo a cikin kamanni na mutane maza, su kuma mutanensa sun jarrabu da neman maza da lalata. Bayan mala’ikun sun fahimci damuwarsa sai suka kwantar masa da hankali suka nuna masa kada ya ji tsoro, mutanensa ba za su iya cutar da shi ba, kuma su mala’iku ne, sun zo ne don su hallaka mutanensa kuma za su tserar da shi tare da iyalansa duka in ban da matarsa, ita kam za ta yi saura a cikin mutanensa, don haka za ta hallaka tare da su. Suka kuma yi masa bayanin irin azabar da aka umarce su da su saukar wa mutanensa, watau azabar ruwan duwatsu na wuta daga sama bayan an ɗaga garin sama an kifar da shi saboda fasiƙancin da suke aikatawa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lalle ya bar bayyananniyar aya ga mutanen da suke da hankali masu ɗaukar izina da darasi daga ayoyin Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk annabawan Allah sun fara da'awarsu ne da kira zuwa ga Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta da guje wa bautar waninsa.

2. Mutanen Annabi Shu'aibu ba su yi imani da ranar alƙiyama ba.

3. Yana daga cikin manufofin da'awar annabawa daƙile yaɗa ɓarna a bayan ƙasa.

Suratul Ankabut (36-37)
وَإِلَىٰ مَدۡيَنَ أَخَاهُمۡ شُعَيۡبٗا فَقَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱرۡجُواْ ٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَلَا تَعۡثَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُفۡسِدِينَ ٣٦ فَكَذَّبُوهُ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلرَّجۡفَةُ فَأَصۡبَحُواْ فِي دَارِهِمۡ جَٰثِمِينَ ٣٧

36. Mun kuma (aika wa mutanen) Madyana ɗan'uwansu Shu'aibu, sai ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah, kuma ku yi fatan (kyakkyawan samakon) ranar lahira, kada kuma ku riƙa yaɗa ɓarna a bayan ƙasa."

37. Sai suka ƙaryata shi, sai girgizar ƙasa ta kama su, suka wayi gari duddurƙushe (matattu) cikin gidajensu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya aika wa mutanen Madyana ɗan'uwansu na jini Annabi Shu'aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai ya umarce su da su bauta wa Allah shi kaɗai ba shi da abokin tarayya, kuma su yi kwaɗayin kyakkyawan sakamakon ranar lahira, da bautar da za su yi wa Allah, ya kuma hana su yaɗa ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar kafirci da saɓon Allah.
Daga cikin ɓarnar da suke yaɗawa a bayan ƙasa akwai tauye wa mutane haƙƙoƙinsu na awo da tsare hanyoyi suna yi wa mutane fashi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mutanen Annabi Shu'aibu sun ƙaryata shi, sai azabar girgizar ƙasa ta auka musu, sai suka wayi gari a duddurƙushe a gidajensu duk sun hallaka babu mai sauran motsi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Larabawa suna da masaniya game da gidajen Adawa da Samudawa ta hanyar tafiye-tafiyensu da ta hanyar labarai da suke zuwa gare su ta hannun matafiyan cikinsu.

2. Hankali da basira ba za su yi wa mutum amfani ba matuƙar ya rasa imani da Allah.

3. Allah bai hallakar da al'ummun da suka kafirce masa ba har sai bayan da ya yanke musu hanzari, ya nuna musu ayoyinsa bayyanannu waɗanda za su iya fahimta.

4. Ganin gidajen waɗanda aka hallakar wa'azi ne ga masu hankali, kamar yadda ake cewa "gani ga wane ya ishi wane tsoron Allah".

5. Ɓacewar Adawa ya samo asali ne daga lalacewar aƙidunsu da kuma kafircin da suka gada iyaye da kakanni, ba su kuɓuta daga azabar Allah ba domin suna da hankalin da za su yi tunani da shi su gane Kaɗaitakar Allah da gaskiyar manzanninsa.

6. Kamar yadda Allah ya ba wa ƙabilar Kuraishawa misali da al'ummun da suka kafirce masa kuma ya hallaka su, hakanan ya ba wa manyan Kuraishawa misali, irin su Abu Jahal da Umayyatu ɗan Khalaf da Al-Walid ɗan Mugira, ya ba su misali da wasu manya-manyan kafirai na al'ummun da suka shuɗe waɗanda ya hallaka, kamar su Karuna da Hamana da sauransu waɗanda musifarsu ba ta tsaya a kansu su kaɗai ba, har sai da ta shafi mutanensu waɗanda suka bi su a kan ɓata. Wannan gargaɗi ne ga Kuraishawa da su guji biyayya ga shugabanninsu a kan kafirci domin za su kai su ne zuwa ga hallaka.

Suratul Ankabut (38-40)

وَعَادًا وَثَمُودَاْ وَقَد تَّبَيَّنَ لَكُم مِّن مَّسَٰكِنِهِمۡۖ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَعۡمَٰلَهُمۡ فَصَدَّهُمۡ عَنِ ٱلسَّبِيلِ وَكَانُواْ مُسۡتَبۡصِرِينَ ٣٨ وَقَٰرُونَ وَفِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَۖ وَلَقَدۡ جَآءَهُم مُّوسَىٰ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَٱسۡتَكۡبَرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا كَانُواْ سَٰبِقِينَ ٣٩ فَكُلًّا أَخَذۡنَا بِذَنۢبِهِۦۖ فَمِنۡهُم مَّنۡ أَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِ حَاصِبًا وَمِنۡهُم مَّنۡ أَخَذَتۡهُ ٱلصَّيۡحَةُ وَمِنۡهُم مَّنۡ خَسَفۡنَا بِهِ ٱلۡأَرۡضَ وَمِنۡهُم مَّنۡ أَغۡرَقۡنَاۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٤٠

38. Kuma (Mun hallaka) Adawa da Samudawa, haƙiƙa (abin da ya faru a gare su) ya bayyana gare ku a fili a gidajensu; kuma Shaiɗan ya ƙawata musu ayyukansu, sai ya kange su daga hanya (madaidaiciya), sun kuma kasance masu gani da basirarsu (amma suka zaɓi ɓata).

39. Kuma (Mun hallaka) Karuna da Fir'auna da Hamana; haƙiƙa kuma Musa ya zo musu da hujjoji bayyanannu, sai suka yi girman kai a bayan ƙasa, kuma ba su kasance masu guje wa (azaba) ba.

40. Kowanne (cikin al'ummun da suka gabata) Mun kama shi da laifinsa; daga cikinsu akwai waɗanda Muka aiko wa da duwatsu, akwai kuma waɗanda tsawa ta kama su, kuma daga cikinsu akwai waɗanda Muka kifar da su cikin ƙasa, akwai kuma daga cikinsu waɗanda Muka nutsar a ruwa. Allah kuma bai kasance Yana zaluntar su ba, sai dai kawai kawunansu suke zalunta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci Adawa mutanen Annabi Hudu da Samudawa mutanen Annabi Salihu don ya ƙara tabbatar wa Kuraishawa cewa ya hallaka su yayin da suka kafirce wa annabawansu, kuma abin da ya faru da su na hallakarwa kafiran Kuraishawa sun gan shi a fili a mazaunan Adawa da Samudawa, domin suna kan hanyoyinsu na tafiya fatauci zuwa Yaman da Sham. Suna ganin kufaifan gidajensu babu kowa a cikinsu. Shaiɗan ne ya ƙawata musu miyagun ayyukansu na kafirci da saɓon Allah sai suka riƙa ɗauka wani abu ne mai kyau suke aikatawa, Shaiɗan ya raba su da tafarki madaidaici, alhali manzanninsu sun zo musu da ayoyi bayyanannu waɗanda suke cike da basira da hankali da za su samu damar bambance tsakanin ƙarya da gaskiya da kuma ɓata da shiriya. To amma sai suka zaɓi su bi son zuciyarsu a maimakon shiriya, don haka ba su da wani hanzari a wurin Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci cewa ya hallaka Karuna yayin da ya nuna zaluncinsa ga mutanensa a fili, ya kifar da shi har da gidansa suka nutse cikin ƙasa. Haka kuma ya hallaka Fir'auna da wazirinsa Hamana lokacin da ya aika musu Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ayoyi bayyanannu masu nuna gaskiyar manzancinsa, amma sai suka nuna girman kai a ƙasar Masar, suka ki yin imani da Annabi Musa, don haka ba su iya kuɓuce wa azaba ba yayin da ta zo musu, sai Allah ya nutsar da su a cikin ruwa suka hallaka gaba ɗayansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin hanyoyin da ya hallaka dukkan waɗancan al'ummu da suka ƙaryata manzanninsu a dunƙule. Daga cikinsu akwai mutanen Annabi Luɗu waɗanda Allah ya aiko musu ruwan duwatsu irin na soyayyen yumɓu. Daga cikinsu akwai mutanen Annabi Salihu da mutanen

Annabi Shu’aibu waɗanda Allah ya hallaka su da tsawa. Daga cikinsu akwai Karuna wanda Allah ya nutsar da shi a cikin ƙasa daga shi har dukiyarsa da gidansa. Daga cikinsu kuma akwai mutanen Annabi Nuhu da Fir’auna da Hamana waɗanda Allah ya nutsar da su a ruwa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ba zai yiwu haka kawai ya zalunce su ya hallakar da su ba laifin zaune ba na tsaye ba, sai dai kawai su ne suka zalunci kawunansu ta hanyar kafirci da ayyukan saɓon Allah, don haka suka cancanci azabarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gurguwar dabarar masu bauta wa wasu ba Allah ba suna zaton za su amfane su ko su kare musu wata cuta, alhalin sun riƙe banza ne babu amfanin da za su iya yi musu.

2. Fahimtar misalan da Alƙur’ani yake ambata dalili ne da yake nuna ilimin mutum da kamalar hankalinsa. Rashin fahimtar su kuwa alama ce ta rashin ilimi da tawayar hankali.

3. Wajabcin karatun Alƙur’ani da bibiyar ma’anoninsa domin aiki da shi.

4. Wajabcin tsai da salla da kulawa da haƙƙoƙinta.

5. Muhimmancin salla wajen gyara tarbiyyar mumini da hana shi aikata miyagun ayyuka.

Suratul Ankabut (41-45)
مَثَلُ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوۡلِيَآءَ كَمَثَلِ ٱلۡعَنكَبُوتِ ٱتَّخَذَتۡ بَيۡتٗاۖ وَإِنَّ أَوۡهَنَ ٱلۡبُيُوتِ لَبَيۡتُ ٱلۡعَنكَبُوتِۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٤١ إِنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ مِن شَيۡءٖۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٤٢ وَتِلۡكَ ٱلۡأَمۡثَٰلُ نَضۡرِبُهَا لِلنَّاسِۖ وَمَا يَعۡقِلُهَآ إِلَّا ٱلۡعَٰلِمُونَ ٤٣ خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ ٤٤ ٱتۡلُ مَآ أُوحِيَ إِلَيۡكَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَۖ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ تَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِۗ وَلَذِكۡرُ ٱللَّهِ أَكۡبَرُۗ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا تَصۡنَعُونَ ٤٥

41. Misalin waɗanda suka riƙi wasu iyayen giji ba Allah ba, kamar misalin gizogizo ne da ya saƙa gida; haƙiƙa kuwa lalle gidan gizogizo shi ya fi kowanne gida rauni, da sun kasance suna sanin (haka).

42. Lalle Allah Yana sane da kowane abu da suke bauta wa wanda ba Shi ba. Kuma Shi ne Mabuwayi, Mai hikima.

43. Waɗancan misalan Muna ba da su ne ga mutane; ba kuwa wanda yake hankaltar su sai malamai kawai.

44. Allah Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga muminai.

45. Ka karanta abin da ake yi maka wahayinsa na Alƙur’ani, ka kuma tsai da salla; lalle salla tana hana alfasha da kuma abin ƙi. Kuma tabbas ambaton Allah shi ne mafi girma. Kuma Allah Yana sane da abin da kuke aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin waɗanda suka riƙi wasu ababen bauta ba Allah ba suna tsammanin za su sami wata kariya ko wani amfani daga gare su. Allah ya kwatanta misalinsu da gizogizo wanda yakan saƙa gidansa da nufin ya kare masa sanyi ko zafi ko iska ko ruwan sama, ko ya kare shi daga wanda zai kai masa harin ta’addanci, to amma daga ƙarshe ba zai samu kariya daga waɗannan abubuwan ba, domin duk a cikin gidajen ƙwari da na dabbobi babu wanda rauninsa ya kai na gidan

gizogizo. To hakanan su ma mushirikai, ababen shirkarsu ba za su amfane su da komai ba, da a ce sun san haka da ba su riƙe su ababen bauta ba Allah ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yana sane da duk wani abu da suke bauta wa ba shi ba, babu abin da yake ɓuya a gare shi, kuma shi ne mabuwayi da babu mai gagararsa ko ya rinjaye shi, kuma mai hikima ne cikin ayyukansa da tsarinsa.
Sai kuma Allah ya bayyana cewa irin waɗannan misalan da yake bayarwa a Alƙur'ani domin jan hankali da faɗakarwa da tabbatar da gaskiya da rushe ɓarna, babu mai fahimtar su yadda ya dace har su amfane shi sai mutanen da Allah ya ba su ilimin sanin shari'arsa da hikimarsa cikin halittunsa.
Sai kuma Allah ya bayyana wata hikimar tasa ta halittar sammai da ƙasa ya tabbatar da cewa ya halicce su ne da gaskiya, watau bai halicce su don wasa ba ko kuma ba don wani amfani ba. Ya tabbatar da cewa lalle a cikin halittarsu da ya yi akwai ayoyi bayyanannu masu nuna girman Kudurarsa da isar ikonsa ga mutane muminai, domin su ne suke kafa hujja a kan samuwar mahalicci da halittarsa. Amma kafirai sai dai su yi ta ganin halittun Allah a sama da ƙasa da kawunansu amma ba sa ɗaukar wata izina ko wani darasi daga gare su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya karanta wa mutane Alƙur'ani da ya yi masa wahayinsa, ya kuma tsayar da salla yadda ya kamata da rukunanta da sharuɗanta da mustahabbanta, kuma lalle ita salla idan ana yin ta yadda ya dace to tana hana mai yin ta faɗawa cikin saɓon Allah da munanan ayyuka, domin tana samar da wani haske a cikin zukata wanda yake tsare bawa daga aikata saɓon Allah, yake kuma ƙarfafa masa yin ayyuka na ƙwarai.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wani mutum ya zo wajen Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle wani yana yin sallar dare amma idan gari ya waye sai ya riƙa yin sata." Sai Manzon Allah ya ce: "Lalle da sannu abin da kake faɗa (watau sallarsa cikin dare) za ta hana shi (sata)." [Ahmad #9778 da Ibn Hibban #2560].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lalle ambaton Allah shi ne ya fi komai girma. Kuma Allah ya san abin da mutane suke aikatawa, zai kuma saka wa kowa a kan ayyukansa kyawawa da munana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni da yin jayayya da ma'abota littafi ta hanya mafi kyau sai dai waɗanda suka bayyana zaluncinsu da taurin kansu, to su za a bi da su ta hanyar da ta dace da su.

2. Imanin mumini ba zai inganta ba har sai ya yi imani da duk manzannin Allah da littattafansu.

3. Ba daidai ba ne jayayya da ma'abota littafi ta kai ga sukan wani littafi daga littattafan da Allah ya saukar ko sukan wani daga cikin manzanninsa. Wajibi ne yayin jayayya da wani abokin husuma a yi watsi da duk wata ƙarya da ya kawo a karɓi gaskiyar da ta fito daga bakinsa ko da kuwa shi kafiri ne.

4. Duk wata hujja da ta tabbatar da annabcin wani daga cikin annabawan Allah, to akwai irinta ko ma wadda ta fi ta mai tabbatar da annabcin Annabi Muhammadu (ﷺ). Hakanan duk wata shubuha da za a soki annabcin Annabi Muhammadu (ﷺ) da ita to akwai irinta ko ma wadda ta fi ta da za a iya sukan annabcin kowane annabi da ita. Idan har ya tabbatar wannan shubuhar ƙarya ce game da wani annabi, to tabbatar zamantowarta ƙarya game da Annabi Muhammadu (ﷺ) ta fi fitowa ƙarara.

5. Tabbatar da zamantowar Manzon Allah (ﷺ) ummiyyi wanda ba ya karatu ba ya rubutu har ya koma ga Allah.

6. Alƙur’ani ba zai gushe ba a tsare kuma a haddace a zukatan wasu daga cikin muminai har lokacin da Allah zai ɗauke abinsa. Wannan ɗaya ne daga cikin hanyoyin tsare shi.

7. Kwaɗaitarwa a kan haddace ilimi.

Suratul Ankabut (46-49)

*وَلَا تُجَٰدِلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ إِلَّا بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُ إِلَّا ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنۡهُمۡۖ وَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَأُنزِلَ إِلَيۡكُمۡ وَإِلَٰهُنَا وَإِلَٰهُكُمۡ وَٰحِدٞ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ٤٦ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَۚ فَٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۖ وَمِنۡ هَٰٓؤُلَآءِ مَن يُؤۡمِنُ بِهِۦۚ وَمَا يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا ٱلۡكَٰفِرُونَ ٤٧ وَمَا كُنتَ تَتۡلُواْ مِن قَبۡلِهِۦ مِن كِتَٰبٖ وَلَا تَخُطُّهُۥ بِيَمِينِكَۖ إِذٗا لَّٱرۡتَابَ ٱلۡمُبۡطِلُونَ ٤٨ بَلۡ هُوَ ءَايَٰتُۢ بَيِّنَٰتٞ فِي صُدُورِ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَۚ وَمَا يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا ٱلظَّٰلِمُونَ ٤٩

46. Kuma kada ku yi jayayya da ma’abota littafi (Yahudu da Nasara) sai ta hanyar da ta fi kyau, sai dai waɗanda suka yi zalunci daga cikinsu; kuma ku ce: “Mun yi imani da abin da aka saukar mana da kuma abin da aka saukar muku, kuma Abin bautarmu da Abin bautarku Ɗaya ne, kuma mu masu miƙa wuya ne gare Shi.”

47. Kamar haka kuma Muka saukar maka da Alƙur’ani. To waɗanda Muka bai wa littafi (a gabaninka) suna imani da shi; daga waɗannan kuma (wato mutanen Makka) akwai wanda yake imani da shi. Ba kuwa mai musun ayoyinmu sai kafirai.

48. Ba ka zamanto kuma kana karanta wani littafi kafinsa ba (wato Alkur’ani), kuma ba ka rubuta shi da hannun damanka; da kuwa haka ya faru, to da sai masu ƙaryatawa su shiga kokwanto.

49. A’a, shi dai (Alƙur’ani) ayoyi ne bayyanannu (da suke) cikin zukatan waɗanda aka bai wa ilimi. Ba kuwa mai yin musun ayoyinmu sai azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗakar da Musulmi kan yadda ya kamata su tattauna da ma’abota littafi, musamman bayan sun yi hijira zuwa Madina inda suka haɗu da Yahudawa mazauna birnin Madina. Allah ya nusantar da muminai da su yi jayayya da su ta hanya mafi kyau, watau wa’azi cikin hikima da tausasa harshe da bayanin hujjoji masu gamsarwa yayin da suka fahimci suna so ne su gane gaskiya. Amma azzalumai daga cikinsu masu taurin kai da ƙoƙarin tayar da fitina ko shirin yaƙar Musulmi, to waɗannan sai a tafiyar da su ta hanyar da ta dace. Idan sun shelanta yaƙi to a yaƙe su har sai sun musulunta ko sun miƙa wuya sun zauna da Musulmi lafiya, sun biya jiziyar da take kansu.
Sai kuma Allah ya nuna wa Musulmi wasu hanyoyi da za su bi na tattaunawa da ma’abota littafi masu son su fahimci gaskiya, ya ce su nuna musu cewa sun yi imani da abin da Allah ya saukar musu, watau Alkur’ani, sun kuma yi imani da abin da su ma ya saukar musu, watau Attaura da Linjila. Sannan su sanar da su cewa dukkansu abin bautarsu ɗaya ne ba shi da abokin tarayya a bautarsa ko siffofinsa da ayyukansa. Don haka su tabbatar musu da cewa su sun miƙa wuya gare shi shi kaɗai.

An karƃo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Ma’abota littafi suna karanta Attaura da harshen Ibraniyanci suna fassara wa Musulmi da Larabci, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kada ku gaskata ma’abota littafi, kada kuma ku ƙaryata su, ku ce: ‘Mun yi imani da abin da aka saukar mana da kuma abin da aka saukar muku, kuma abin bautarmu da abin bautarku ɗaya ne, kuma mu masu miƙa wuya ne gare shi.’” [Bukhari #4485, 7362].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzo (ﷺ) cewa kamar yadda ya saukar wa annabawan da suka gabace shi littattafai hakanan shi ma ya saukar masa Alƙur'ani. To wasu daga cikin ma'abota littafi masu karanta Attaura, irin su Abdullahi ɗan Salam suna yin imani da Annabi (ﷺ) saboda sun karanta siffofinsa a littattafansu. Daga cikin mushirikai ma akwai waɗanda suke yin imani da shi, to amma babu masu musun ayoyin Allah sai tsantsar kafirai masu girman kai masu ƙyamar gaskiya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hujjar da take ƙara tabbatar da cewa Alƙur'ani saukakke ne daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ƙirƙirar Manzon Allah ne ba, ya bayyana wa mushirikai abin da suka riga suka sani na halayensa tun kafin a aiko shi, da cewa ai bai zamanto yana karanta wani littafi ba kafin a saukar masa Alƙur'ani ballantana a ce a ciki ya koya, kuma bai zamanto yana rubuta wani abu da hannunsa ba, domin shi ummiyyi ne ba ya karatu ba ya rubutu. Ashe ba don haka ba da sai jahilai su riƙa shakka game da annabcinsa su fake da cewa Alƙur'anin da yake karanta musu ya samo shi ne daga littattafan magabata.
Sai kuma Allah ya tabbatar da cewa shi Alƙur'ani ayoyi ne bayyanannu a zukatan muminai waɗanda aka ba su ilimi, watau waɗannan su ya kamata a saurari maganarsu ba jahilai ba waɗanda ba su san komai daga ayoyinsa ba, waɗannan maganganunsu ba su da wani tasiri. Ya bayyana cewa babu masu jayayya da ayoyin Allah sai azzalumai waɗanda suka cuci kawunansu da shirka da saɓon Allah.

An karɓo daga Iyadh ɗan Himar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana cewa: "Ni mai jarrabar ka ne mai kuma jarrabar wasu ta sanadiyyarka ne, mai saukar maka da wani littafi ne wanda ruwa ba zai wanke shi ba, za ka riƙa karanta shi kana barci ko kana farke." [Muslim # 2865].

Yana nufin da za a rubuta Alƙur'ani sannan daga baya a wanke shi, to hakan ba zai sa a rasa shi ba, domin yana nan a haddace a zukatan muminai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani mu'ujizar Annabi (ﷺ) ce ta har abada.

2. Alƙur'ani littafi ne mai cike da alheri mai yawa da tarin ilimi mai amfani, don haka ya zamanto rahama ga muminai.

3. Da Annabi (ﷺ) ƙarya yake yi wa Allah game da abin da yake cewa ana yi masa wahayinsa, sannan Ubangiji ya ƙyale shi ba tare da ya saukar masa da azabarsa ba, ya zamanto ma yana ƙarfafar sa da ayoyinsa da nasarori a kan abokan gabarsa, da wannan ya zamanto babban abin suka game da Kudurar Allah da hikimarsa.

Suratul Ankabut (50-52)
وَقَالُواْ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ ءَايَٰتٞ مِّن رَّبِّهِۦۖ قُلۡ إِنَّمَا ٱلۡأٓيَٰتُ عِندَ ٱللَّهِ وَإِنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٞ مُّبِينٌ ٥٠ أَوَ لَمۡ يَكۡفِهِمۡ أَنَّآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ يُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَرَحۡمَةٗ وَذِكۡرَىٰ لِقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٥١ قُلۡ كَفَىٰ بِٱللَّهِ بَيۡنِي وَبَيۡنَكُمۡ شَهِيدٗاۖ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱلۡبَٰطِلِ وَكَفَرُواْ بِٱللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٥٢

50. Suka kuma ce: "Me ya hana a saukar masa da wasu ayoyi daga Ubangijinsa?" Ka ce (da su): "Ayoyi suna wurin Allah ne kawai, ni kuma ba kowa ba ne face mai gargaɗi, mai bayyana (gargaɗin)."

51. Yanzu bai ishe su ba cewa, Mun saukar maka da Littafi da ake karanta musu shi? Lalle a game da wannan tabbas akwai rahama da kuma tunatarwa ga mutanen da suke yin imani.

52. Ka ce (da su): “Allah Ya isa shaida tsakanina da ku; Yana sane da abin da yake cikin sammai da ƙasa. Waɗanda kuwa suka yi imani da ƙarya suka kuma kafirce wa Allah, waɗannan su ne asararru.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk da ƙarfafan hujjoji da suka tabbatar da gaskiyar Manzo (ﷺ) kafirai sun nace da neman ya kawo musu wasu mu’ujizoji daban waɗanda su suka ambata, suna ganin in da gaske ne shi Manzon Allah ne me zai hana Ubangijinsa ya saukar masa da waɗannan ayoyi? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya faɗa musu cewa shi fa ba a hannunsa saukar da wata aya yake ba; wannan yana wurin Allah ne kawai, shi aikin da Allah ya ɗora masa shi ne ya yi gargaɗi ga mutane dangane da azabar Allah in ba su yi imani ba.
Sannan ya sanar da su cewa, yanzu Alƙur’ani da ya saukar masa bai ishe su aya ba? Allah ya nuna girman Alƙur’ani ta hanyar siffanta shi da wasu manyan siffofi kamar haka:
Siffa ta farko, littafi ne da ake karanta musu shi, wannan ya nuna yaɗuwarsa ko’ina a kowane zamani, bai taƙaita ga wasu mutane ban da wasu ba, ga shi kuma ya ƙunshi ƙalubale na a kwaikwaye shi idan an isa, amma hakan bai yiwu ba.
Ta biyu, kasancewar ana karanta shi a koyaushe kuma a ko’ina ya nuna ya fi sauran mu’ujizoji da Allah ya ba wa sauran annabawa, kamar sandar Annabi Musa ko taguwar Annabi Salihu ko warkar da makaho da tayar da matacce da izinin Allah da aka ba wa Annabi Isa. Waɗannan mu’ujizojinsu na gani ne da ido kawai, sun kuma taƙaita a zamaninsu. Amma mu’ujizar Alƙur’ani ta danganci aiki na ƙwaƙwalwa da tunani na hankali wanda ba mai taƙaita ne ba a wani zamani ban da wani ba; yana ɗorewa ne har zuwa tashin ƙiyama.
Ta uku, Alƙur’ani rahama ne, domin ya ƙunshi shari’a wadda take rahama ce ga halittu a kowane lokaci kuma a ko’ina.
Ta huɗu, kuma tunatarwa ne, domin ya ƙunshi wa’azi da nasihu iri-iri da jan hankali game da rayuwar lahira; wannan ya ba shi fifiko a kan sauran mu’ujizoji na annabawa.
Ta biyar, an danganta rahamar Alƙur’ani da tunatarwarsa ga mutane muminai, domin a nuna cewa amfanin da ke cikinsa babu mai morar sa sai wanda ya yi imani da Manzo Allah (ﷺ), domin shi ne zai gaskata shi ya kuma yi aiki da koyarwarsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzo (ﷺ) ya bayyana musu wata ƙaƙƙarfar hujja da ke nuna cewa shi Manzon Allah ne da gaske, watau shaidar da Allah ya yi masa da ta nuna gaskiyarsa ta kuma tabbatar da ƙaryarsu, domin Allah ne wanda ya san abin da yake cikin sammai da ƙasa, ba abin da yake ɓuya a gare shi. Da a ce Manzon Allah (ﷺ) ƙarya yake yi masa da ya fallasa shi, ba zai ƙarfafe shi da ayoyi ba, ba kuma zai yi ta cin nasara ba a kan magabtansa a tsawon rayuwarsa. Sai dai kuma duk da wannan bayani mutanen da suka riga suka yi imani da ƙarya suka rungumi wasu ababen bauta ba Allah ba suka kafirce wa Allah, to waɗannan asararru ne ba za su ci riba ba ko kaɗan, tunda sun fifita kafirci a kan imani da Allah da Manzonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin wautar kafirai da jahilcinsu, yayin da suke neman a gaggauto musu azabar Allah tun a nan duniya, maimakon su roƙi shiriyarsa.

2. Bayani a kan cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai jinkirta musu azaba ba don gazawa, ya yi haka ne domin ya riga ya tsara komai yadda zai gudanar da shi tun fil azal, don haka wautar kafirai da jahilcinsu ba za su sa ya canja tsarinsa ba.

3. Tsananin azabar kafirai a ranar alƙiyama.

Suratul Ankabut (53-55)

وَيَسْتَعْجِلُونَكَ بِٱلْعَذَابِ وَلَوْلَآ أَجَلٌ مُّسَمًّى لَّجَآءَهُمُ ٱلْعَذَابُ ۚ وَلَيَأْتِيَنَّهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ﴿٥٣﴾ يَسْتَعْجِلُونَكَ بِٱلْعَذَابِ وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمُحِيطَةٌۢ بِٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٥٤﴾ يَوْمَ يَغْشَىٰهُمُ ٱلْعَذَابُ مِن فَوْقِهِمْ وَمِن تَحْتِ أَرْجُلِهِمْ وَيَقُولُ ذُوقُوا۟ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٥٥﴾

53. Suna kuma neman ka da ka gaggauto musu da azaba. Ba don kuwa akwai lokaci na musamman (da aka tanada) ba, tabbas da azabar ta zo musu, kuma tabbas da za ta zo musu ne ba zato ba tsammani, alhali ba su sani ba.

54. Suna (kuma) neman ka da ka gaggauto musu da azaba, alhali kuwa Jahannama tabbas mai kewaye kafirai ce.

55. A ranar da azaba za ta lulluɓe su ta samansu da ta ƙarƙashin ƙafafuwansu, kuma (Allah) Ya ce (da su): “Ku ɗanɗani abin da kuka kasance kuna aikatawa.”

Bayan Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya mayar wa da kafirai martani a kan neman a saukar masa da wasu mu’ujizoji don su yarda da manzancinsa, sai suka ci gaba da ƙaryata abin da yake yi musu gargaɗi a kansa na uƙubar Allah idan sun ƙi yin imani, har ma suna neman sa da ya gaggauto musu da azabar in da gaske ne abin da yake faɗa, kada ya jira har sai an je lahira, domin su ba su ma yarda akwai ranar alƙiyama ba ballantana a yi musu hisabi. Sai Allah ya amsa musu da cewa ba abu ne da zai gagare shi ba ya saukar musu da azabar da suke nema, sai dai kawai komai ya sanya masa lokaci wanda ba ya gaggauto shi kafin ya zo kuma ba ya jinkirta shi idan ya zo, amma su san da cewa lalle azabar nan sai ta auko musu ba zato ba tsammani.
Ya kuma bayyana musu cewa su daina wata gaggawa don ganin wata gamammiyar azaba ba ta sauka a kansu a nan duniya ba, su sani akwai azabar lahira tana nan tana jiran su, domin lalle Jahannama a kewaye take da su ta ko’ina, ba wurin gudu ko tsere mata.
Ya kuma tabbatar musu da cewa wannan azabar ta lahira matsananciya ce, kuma za ta same su ta lulluɓe su ta samansu ta yi musu rumfa, ta ƙasansu kuwa ta zame musu shimfiɗa, Allah kuma ya riƙa ce musu: “Ku ɗanɗani abin da kuka kasance kuna aikatawa”, watau babu wanda ya zalunce su, su dai ne suka zalunci kawunansu da kafirci da aikata shirka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kofar yin hijira don kuɓuta da addini a buɗe take, babu wani hanzari ga mutumin da zai bar bautar Allah don an hana shi, alhalin akwai inda yake da damar ya yi hijira ya samu ‘yancin yin addininsa.

2. Falalar haƙuri da dogaro ga Allah.

3. Arzikin kowa yana hannun Allah, shi ne mai bayarwa shi ne mai hanawa.

Suratul Ankabut (56-60)

يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِنَّ أَرْضِى وَٰسِعَةٌ فَإِيَّٰىَ فَٱعْبُدُونِ ﴿٥٦﴾ كُلُّ نَفْسٍ ذَآئِقَةُ ٱلْمَوْتِ ۖ ثُمَّ إِلَيْنَا تُرْجَعُونَ ﴿٥٧﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُبَوِّئَنَّهُمْ مِّنَ ٱلْجَنَّةِ غُرَفًا تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۚ نِعْمَ أَجْرُ ٱلْعَٰمِلِينَ ﴿٥٨﴾ ٱلَّذِينَ صَبَرُوا۟ وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ ﴿٥٩﴾ وَكَأَيِّن مِّن دَآبَّةٍ لَّا تَحْمِلُ رِزْقَهَا ٱللَّهُ يَرْزُقُهَا وَإِيَّاكُمْ ۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٦٠﴾

56. Ya ku bayina waɗanda suka yi imani, lalle ƙasata yalwatacciya ce, to Ni kaɗai sai ku bauta Mini.

57. Kowanne rai zai ɗanɗani mutuwa; sannan wurinmu za a mayar da ku.

58. Waɗanda kuma suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, lallai za Mu zaunar da su cikin manya-manyan gidaje a Aljanna (waɗanda) ƙoramu za su riƙa gudana ta ƙarƙashinsu suna madawwama a cikinsu. Madalla da ladan masu aiki (nagari).

59. (Su ne) waɗanda suka yi haƙuri, kuma ga Ubangijinsu kawai suka dogara.

60. Sau tari ga dabba nan da ba za ta iya ɗaukar arzikinta ba, Allah ne Yake arzuta ta har da ku. Shi ne Mai ji, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira bayinsa waɗanda suka yi imani da shi, suka kuma yi imani da Manzonsa (ﷺ) amma suna zaune a cikin kafirai suna tsangwamar su a kan addininsu har ma suna ƙoƙarin su hana su bautar Allah shi kaɗai, to sai ya umarce su da yin hijira zuwa inda za su sami ‘yancin bautar Allah shi kaɗai ba tare da tsangwama ba domin ƙasarsa mai yalwa ce.
Sai kuma ya nuna musu cewa, kada tsoron mutuwa ya hana su yin hijira da gujewa su tsira da addininsu, domin ita mutuwa rigar kowa ce, duk wani mai rai sai ya ɗanɗane ta, sannan daga ƙarshe duk za a mayar da su ne zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ranar alƙiyama don a yi musu hisabi a kan ayyukansu, a bayyana sakamakon waɗanda suka yi imani tare da ayyuka nagari, a shigar da su ɗakunan Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, su zauna a cikinsu zama na har abada babu mutuwa. Allah kuma ya yi musu sam-barka a kan wannan kyakkyawan sakamako da zai ba wa waɗanda suka yi ayyukan ɗa’a gare shi.
Allah ya siffanta waɗannan bayi nasa masu rabauta da wannan gwaggwaɓan sakamako da cewa su ne waɗanda suka yi haƙuri a kan yi masa biyayya da kauce wa saɓa masa, da haƙuri game da cutarwar mushirikai a gare su. Su ne kuma masu dogaro ga Allah shi kaɗai cikin dukkan al’amuransu.
Sai kuma Allah ya ƙara jan hankalin muminai a kan kada tsoron talauci ko yunwa ya hana su yin hijira zuwa inda za su bauta masa shi kaɗai, ya bayyana musu cewa da yawa daga cikin dabbobi waɗanda ba za su iya ciyar da kansu ba ko su tara wa kansu arziki, Allah ne yake ciyar da su, kuma su ma mutanen shi ne yake ciyar da su, don haka ba su da wani hanzari na ƙin yin hijira don tsoron talauci ko yunwa. Sannan ya tabbatar musu da cewa shi mai jin duk maganganun da suke furtawa ne, masanin niyyoyinsu da ayyukansu ne, zai kuma yi musu sakayya a kan haka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yarda da Rububiyyar Allah da musunta Uluhiyyarsa, watau kaɗaita shi da bauta, ba abu ne da zai samar wa da bawa tsira a wurin Allah ba, kuma ba zai tabbatar da imaninsa ba.

2. Mushirikan Kuraishawa sun yarda da Tauhidin Rububiyya, watau kaɗaita Allah da ayyukansa, kamar halittar sammai da ƙasa da rayawa da kashewa da saukar da ruwan sama, amma sun ƙaryata kaɗaita shi wajen bauta sai imaninsu da Rububiyya bai amfane su da komai ba.

3. Allah ne mai ba da arziki, shi ne kuma mai hanawa. Samu da rashi ba sa nuna yardar Allah ko fushinsa ga bawansa.

Suratul Ankabut (61-63)

وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَسَخَّرَ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُۖ فَأَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿٦١﴾ ٱللَّهُ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ وَيَقْدِرُ لَهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ﴿٦٢﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّن نَّزَّلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَحْيَا بِهِ ٱلْأَرْضَ مِنۢ بَعْدِ مَوْتِهَا لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُۚ قُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿٦٣﴾

61. Tabbas da za ka tambaye su: “Wane ne ya halicci sammai da ƙasa, ya kuma hore rana da wata?” To tabbas za su ce: “Allah ne.” To ta yaya ake karkatar da su (daga kaɗaita Shi)?

62. Allah Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama daga bayinsa, Ya kuma ƙuntata masa. Lalle Allah Masanin komai ne.

63. Kuma tabbas da za ka tambaye su: “Wane ne ya saukar da ruwa daga sama, sai ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta?” Lalle za su ce: “Allah ne.” Ka ce (da su): “*Alhamdu Lillahi*.” A’a, yawancinsu dai ba sa hankalta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda mushirikan Larabawa suka riƙa tufka da warwara game da Tauhidi. Domin idan da Manzon Allah (ﷺ) zai tambaye su wane ne ya halicci sammai da ƙasa, ya kuma hore rana da wata suna maye gurbin juna? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa za su amsa masa da cewa Allah ne ya halicce su. To in haka ne me ya sa ake karkatar da su daga yin imani da Kaɗaitakarsa, har suke bauta wa wasu iyayen giji ba shi ba?
Sai ya tabbatar musu da cewa shi ne yake yalwata arzikinsa ga wanda ya ga dama daga bayinsa, yake kuma ƙuntata wa wanda ya ga dama saboda wata hikima da shi kaɗai ya san ta, saboda lalle shi masanin komai ne dangane da hanyoyin gudanar da al’amuran bayinsa yadda ya dace da rayuwarsu a bayan ƙasa, babu abin da ya gagare shi.
Sai kuma ya bayyana cewa da Manzon Allah (ﷺ) zai tambaye su cewa wane ne ya saukar da ruwa daga sama wanda da shi ne ya fitar da tsirrai daga ƙasa bayan ta bushe ƙayau? Allah ya tabbatar masa da cewa lalle amsarsu ita ce, Allah ne ya yi hakan. Sai ya umarci Manzonsa da ya yabi Ubangiji ya gode masa game da hujja mabayyaniya da ya ba shi a kansu, ya kuma bayyana masa cewa yawancinsu ba sa hankalta, ba don haka ba da ba su riƙa bautar gumaka tare da Allah ba alhalin suna ganin ba sa amfanar su da komai, kuma ba sa iya cutar da su da komai ballantana su ji tsoron su su bauta musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a kan guje wa ruɗuwa da rayuwar duniya.

2. Koma-bayan rayuwar duniya mai ƙarewa idan an kwatanta ta da rayuwar lahira mai dawwama har abada.

3. Yayin da mushirikai suka shiga cikin wani hatsari sukan komo ga Allah shi kaɗai su watsar da duk wani abin bauta ba Allah ba. Wannan ya nuna yadda aƙidarsu take cike da tufka da warwara.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan amsa addu’ar wanda ya shiga cikin matsuwa, ya kuma tsantsanta addu’arsa gare shi, ko da kuwa shi kafiri ne.

5. Bayanin girman sha’anin ikhlasi da muhimmancinsa a wurin Allah.

6. Butulcin kafirai ga ni’imomin da Allah yake musu.

Suratul Ankabut (64-66)

وَمَا هَٰذِهِ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَآ إِلَّا لَهۡوٞ وَلَعِبٞۚ وَإِنَّ ٱلدَّارَ ٱلۡأٓخِرَةَ لَهِيَ ٱلۡحَيَوَانُۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٦٤ فَإِذَا رَكِبُواْ فِي ٱلۡفُلۡكِ دَعَوُاْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ فَلَمَّا نَجَّىٰهُمۡ إِلَى ٱلۡبَرِّ إِذَا هُمۡ يُشۡرِكُونَ ٦٥ لِيَكۡفُرُواْ بِمَآ ءَاتَيۡنَٰهُمۡ وَلِيَتَمَتَّعُواْۚ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ٦٦

64. Kuma wannan rayuwar duniya ba komai ba ce face sharholiya da wasa. Kuma lalle (rayuwar) gidan lahira ita ce rayuwa, in da sun kasance sun sani.

65. To idan suka hau jiragen ruwa sukan roƙi Allah suna masu tsantsanta addini a gare Shi; to lokacin da Ya tserar da su zuwa tudu sai ga su suna yin shirka.

66. Don su kafirce wa abin da Muka ba su, kuma don su ji daɗi; to da sannu za su sani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana matsayin rayuwar duniya da zamantowarta ba komai ba idan an kwatanta ta da rayuwar lahira. Ya siffanta rayuwar duniya da cewa ita sharholiya ce kawai da wasa, saboda abin da ke cikinta na sha’awace-sha’awace da ƙyale-ƙyale masu ɗaukan hankali da ruɗi. Rayuwa ta haƙiƙa ita ce rayuwar lahira wadda ba ta da ƙarshe. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa da kafirai sun san zaɓen tumun daren da suka yi da ba su fifita rayuwar duniya a kan ta lahira ba; da ba su ɗauki mai gushewa ba sun bar mai dawwama.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata tufka da warwara ta mushirikan Kuraishawa game da kaɗaita Allah da ikhlasi wajen roƙon sa da cewa, idan suka shiga jirgin ruwa ya fara tangal-tangal da su, suka hango hallaka a fili, sai su kira Allah shi kaɗai suna masu tsantsanta addu’arsu a gare shi, domin ya tserar da su daga nutsewa a ruwa, sai su manta da allolinsu. Amma da zarar ya kuɓutar da su daga hallaka sun haye tudu, sai su koma su ci gaba da bautar gumakansu, suna kuma yin haka ne don su butulce wa ni’imomin da Allah ya yi musu. Sai Allah ya yi musu talala da cewa su je su yi ta more abin da aka ba su na jin daɗin duniya, ba da jimawa ba za su gane babban kuskuren da suka tafka a rayuwarsu lokacin da mutuwa ta zo musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsare garin Makka daga duk wani wanda zai nufe shi da sharri ko zalunci.

2. Bayanin butulcin Kuraishawa ga ni’imar tsaro da Allah ya ba su tun kafin zuwan Manzon Allah (ﷺ), yayin da sauran garuruwa suka rasa haka.

3. Muhimmancin tsaro da kwanciyar hankali a rayuwar ɗan’adam.

4. Mafi girman zalunci shi ne yi wa Allah ƙarya, ko ƙaryata wahayinsa da yake yi wa manzanninsa.

5. Duk wanda ya miƙe tsaye ya yi fafutukar neman shiriya wajen Allah, to lalle Allah zai nuna masa hanyar shiriya.

6. Girman sakamakon ihsani.

Suratul Ankabut (67-69)

أَوَ لَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّا جَعَلۡنَا حَرَمًا ءَامِنٗا وَيُتَخَطَّفُ ٱلنَّاسُ مِنۡ حَوۡلِهِمۡۚ أَفَبِٱلۡبَٰطِلِ يُؤۡمِنُونَ وَبِنِعۡمَةِ ٱللَّهِ يَكۡفُرُونَ ٦٧ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوۡ كَذَّبَ بِٱلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَهُۥٓۚ أَلَيۡسَ فِي جَهَنَّمَ مَثۡوٗى لِّلۡكَٰفِرِينَ ٦٨ وَٱلَّذِينَ جَٰهَدُواْ فِينَا لَنَهۡدِيَنَّهُمۡ سُبُلَنَاۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَمَعَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٦٩

67. Yanzu ba su ga cewa, Mu Muka sanya musu Harami amintacce ba, alhali kuwa ana ta fauce mutane a kewayensu? Shin yanzu sa rika yin imani da karya su kuma rika kafirce wa ni'imar Allah?

68. Wane ne ya fi zalunci kamar wanda ya kaga wa Allah karya ko kuma ya karyata gaskiya lokacin da ta zo masa? Yanzu ashe babu mazaunar kafirai a cikin Jahannama?

69. Waɗanda kuma suka yi jihadi saboda Mu to tabbas za Mu shiryar da su hanyoyinmu, kuma lalle Allah Yana tare da masu kyautatawa.

A ayoyin karshe na wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata babbar ni'ima da ya yi wa Kuraishawa amma suke butulce masa suna kafirce wa Manzonsa (ﷺ). Allah ya tunatar da su ni'imar zaman lafiya da ya yi musu a garin Makka, babu mai zubar da jininsu ko ya kwace musu dukiyarsu, a yayin da sauran garuruwa ake ta kai musu hare-hare ana kashe su ana kama su ribatattun yaki, ana kuma kama matansu da 'ya'yansu a matsayin bayi, sannan a wawashe musu dukiyoyinsu. Amma duk wannan ni'imar ba sa ganin ta, sun rungumi allolin karya suna imani da su suna bautar su suna kuma butulce wa ni'imar Allah ba sa gode masa ko kaɗan.
Sai kuma Allah ya bayyana cewa babu azzalumin da ya kai wanda zai kirkiri karya ya jingina wa Allah, ya ce wai Allah yana da abokin tarayya ko yana da ɗa, ko kuma ya karyata gaskiyar da Manzon Allah (ﷺ) ya zo masa da ita. Allah ya tabbattar musu da cewa lalle a Jahannama akwai mazaunar kafirai da makamantansu.
Sai kuma Allah ya bayyana makomar muminai da sakamakonsu da cewa, duk waɗanda suka yi gwagwarmaya saboda shi, suka bar garuruwansu na haihuwa, suka yi jihadi da dukiyoyinsu da rayukansu, tabbas zai shiryar da su hanyoyinsa na alheri, su dace da bin tafarki madaidaici, kuma lalle shi yana tare da masu kyautatawa da taimakonsa da nasararsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Labarai na gaibu da Alkur'ani ya bayar babban dalili ne mai tabbatar da cewa daga Allah yake, ba zancen wani mutum ne ba.

2. Nuna kusancin ma'abota littafi ga Musulmi fiye da mushirikai masu bautar gumaka ko rana da wata da wuta, ko kuma mulhidai waɗanda ba su yi imani akwai Allah ba.

3. Bayani a kan cewa yawancin mutane ba su san abin da zai sanya su samu kyakkyawar rayuwa ta lahira ba, don haka ne ba su san abin da zai inganta imaninsu ba, ba su da masaniya dangane da shari'ar Allah ko halaye masu kyau. Amma kuma sun san zahirin rayuwar duniya wadda ta danganci tattalin arzuki, kamar noma da sana'a da kasuwanci da sauran fannonin ilimi na rayuwar duniya. [Dubi, *As-Si'idi*, Tafsiri, shafi na 636].

4. Bayani a kan cewa ilimin da Alkur'ani da sunna suka yabi masu shi, suka ɗaukaka darajarsu, shi ne ilimin sanin shari'ar Allah, duk wanda bai san komai game da Allah da Manzonsa da addininsa ba, to wannan jahili ne kowane irin mataki ya taka a ilimin fannoni na rayuwar duniya.

5. Daga cikin mutanen da suka san zahirin rayuwar duniya kawai ba su san Allah ba su ne mutanen da suka danganta komai ga sababba kaɗai, ba tare da suna kawo ganin daman Allah ba, watau mashi’arsa wajen gudanar al’amura. Duk wani sababi ba ya tasiri sai da yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

30-Suratur Rum

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna '*Suratur Rum*' saboda a Alƙur'ani a cikinta ne kawai sunan '*Rum'* ya zo.
2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun yi ittifaƙi a kan cewa Sura ce *Makkiyya*, watau an saukar da ita kafin hijira zuwa Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin da huɗu (84) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratul Inshiƙaƙ*' kafin '*Suratul Ankabut*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta sittin ne (60) a lissafin mutanen Sham da Basra da Kufa. Amma a lissafin mutanen Makka da Madina adadinsu hamsin da tara (59) ne.

5. Sababin Saukarta:
Yaƙi ya ɓarke tsakanin Rumawa ma'abota littafi da Farisawa majusawa masu bautar wuta, sai Farisawa suka yi nasara a kan Rumawa, wannan ya sa mushirikan Larabawa a Makka suka yi farin ciki matuƙa, domin ganin yadda majusawa waɗanda ba su yarda da wani addini saukakke daga sama ba suka yi galaba a kan ma'abota littafi masu bin addinin da Annabi Isa ya zo da shi. Wannan ya sa suka riƙa ganin cewa ashe abin da suke kai na ƙaryata Annabi Muhammadu (ﷺ) shi ne daidai. Sai wannan al'amari ya yi wa Annabi (ﷺ) da sahabbai ciwo, suka yi baƙin ciki ainun, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa a farkon wannan Sura: "ALIF LAM MIM. An yi galaba a kan Rumawa. A ƙasa mafi kusa da (su), su kuma da sannu za su yi galaba (a kan Farisawa) bayan galabar da aka yi a kansu, a cikin 'yan tsirarin shekaru da ba su kai goma ba. Al'amarin na Allah ne, a da da kuma nan gaba. A wannan ranar ne muminai za su yi farin ciki."
Yayin da waɗannan ayoyi suka sauka sai Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) ya shiga cikin saƙo-saƙo na birnin Makka yana karanta su. Da Kuraishawa suka ji shi sai wasu daga cikinsu suke ce masa: "Annabinku ya faɗa muku cewa Rumawa za su ci galaba a kan Farisawa a cikin 'yan tsirarin shekaru, me zai hana mu sanya gasa a kan haka?" Sai Abubakar ya ce ya yarda. A lokacin ba a hana irin wannan gasar mai kama da caca ba. Sai kowa daga cikinsu ya kawo abin da zai saka a gasar, suka yi yarjejeniya a kan haka. Suka kuma tambayi Abubakar cewa shekara nawa za su ɗauka? Sai suka yarda a kan su sanya shekara shida. To da shekara shidan suka zo suka wuce Rumawa ba su yi galaba ba, sai mushirikai suka kwashe dukiyar da Abubakar ya sanya. Amma kuma ana shiga shekara ta bakwai sai Rumawa suka yi galaba a kan Farisawa. A nan Musulmi suka ga baiken Abubakar da ya sanya musu shekara shida bayan kuwa ga shi Allah cewa ya yi a cikin `yan shekaru tsiraru da ba su kai goma ba, watau daga uku har zuwa tara. A dalilin haka kuma mutane da yawa suka karɓi Musulunci. [Dubi, Tirmizi #3194].

6. Babban Jigonta:
Tabbatar da cewa duk al'amura na Allah ne, shi ne mai jujjuya komai a da da yanzu da ma nan gaba.
7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Dakushe farin cikin mushirikai, da faranta wa muminai rai game da galabar da Farisawa suka samu a kan Rumawa, amma Allah ya yi alƙawarin zai ba wa Rumawa nasara a kan Farisawa cikin 'yan shekaru kaɗan.
• Fito da jahilcin mushirikai waɗanda suka kasa fahimtar dalilan da suke jawo rushewar al'umma ko ɗagowarta. Kuma suka kasa ɗaukan wa'azi daga abin da ya sami al'ummun da suka gabace su na hallakarwa saboda shirka da suke yi da Allah.
• Kafa hujja game da tashi bayan mutuwa da kuma Kaɗaitakar Allah ta hanyar bayanin ayoyin Allah wajen tsara gudanar da duniya da tsarin rayuwar ɗan'adam.
• Kwaɗaitar da Manzon Allah (ﷺ) a kan yin riƙo da addini tamau da kuma yabon da ya samu daga Allah.
• Bayanin bambanci da ke tsakanin kyawawan halaye da Musulunci yake kira zuwa gare su da kuma miyagun halaye na mushirikai.
• Bayar da misalai game da yadda Allah yake dawo da rayuwar matattun abubuwa bayan ta gushe da yadda yake samar da ƙarfi bayan rauni, ko rauni bayan ƙarfi.
• Allah ya rufe Surar da sake tabbatar da gaskiyar tashi bayan mutuwa da kuma lallashin Manzon Allah (ﷺ) da yi masa alƙawarin samun nasara a kan abokan gabarsa.

Suratur Rum (1-7)

الٓمٓ ۝١ غُلِبَتِ ٱلرُّومُ ۝٢ فِيٓ أَدۡنَى ٱلۡأَرۡضِ وَهُم مِّنۢ بَعۡدِ غَلَبِهِمۡ سَيَغۡلِبُونَ ۝٣ فِي بِضۡعِ سِنِينَۗ لِلَّهِ ٱلۡأَمۡرُ مِن قَبۡلُ وَمِنۢ بَعۡدُۚ وَيَوۡمَئِذٖ يَفۡرَحُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ۝٤ بِنَصۡرِ ٱللَّهِۚ يَنصُرُ مَن يَشَآءُۖ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ۝٥ وَعۡدَ ٱللَّهِۖ لَا يُخۡلِفُ ٱللَّهُ وَعۡدَهُۥ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ۝٦ يَعۡلَمُونَ ظَٰهِرٗا مِّنَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَهُمۡ عَنِ ٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ غَٰفِلُونَ ۝٧

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ALIF LAM MIM.

2. An yi galaba a kan Rumawa.

3. A ƙasa mafi kusa (da su), su kuma da sannu za su yi galaba (a kan Farisa) bayan galabar da aka yi a kansu.

4. A cikin 'yan tsirarun shekarun (da ba su kai goma ba). Al'amari a da can da nan gaba na Allah ne. A wannan ranar ne muminai za su yi farin ciki.

5. Da samun nasar Allah (a kan Farisa). Shi Yake taimakon wanda Ya ga dama; domin kuwa Shi ne Mabuwayi, Mai rahama.

6. (Wannan ya kasance) alƙawarin Allah ne; Allah ba Ya saɓa alƙawarinsa, sai dai kuma yawancin mutane ba su san (haka) ba.

7. Suna sanin abin da yake a sarari na rayuwar duniya ne, alhali kuwa su gafalallu ne game da lahira.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da wasu haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori a baya da irin waɗannan haruffa. [Duba bayaninsu a farkon *Suratul Bakara*].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin galabar da Farisawa suka samu a kan Rumawa a mafi kusancin lardin Sham da ƙasar Farisa, amma kuma ya tabbatar da cewa daga baya Rumawa su ne za su yi galaba a kan Farisawa a cikin ‘yan shekaru waɗanda ba za su kasa uku ba, ba kuma za su wuce tara ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa dukkan al’amura nasa ne, kafin su ci nasara da kuma bayan sun yi nasara.
Sai kuma ya bayyana cewa ranar da Rumawa za su yi nasara a kan Farisawa abokan faɗansu, a wannan ranar Musulmi za su cika da farin ciki domin ganin cewa Rumawa ma’abota littafi ne kamarsu, watau mabiya addinin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Allah ya tabbatar da cewa shi ne yake ba da nasara ga wanda ya ga dama a kan wanda ya ga dama. Shi kuma mabuwayi ne babu mai iyawa da shi, mai rahama ne ga bayinsa muminai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wannan nasara da zai ba wa Rumawa alƙawari ne da ya ɗaukar wa kansa, kuma duk sanda wannan alƙawari ya tabbata, to farin cikin muminai zai ƙaru da yaƙininsu game da gaskiyar alƙawarinsa, to amma duk da haka yawancin mutane saboda kafircinsu ba sa fahimtar haka.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yawancinsu ba sa yin imani da hukunce-hukuncen shari’a. Abin da kawai suka sani shi ne yadda za su shirya wa kawunansu rayuwar duniya da gina ta da samar da abubuwan more rayuwa, amma kuma dangane da rayuwar lahira wadda ita ce rayuwa ta haƙiƙa mai ɗorewa masu bijirewa ne, wannan rayuwar ba ta gabansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ayoyin Allah waɗanda suke ƙunshe cikin halittar ɗan’adam kaɗai sun isa su nuna Kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da cancantar a bauta masa shi kaɗai.

2. Duk da yawan dalilai masu nuna gaskiyar tashi bayan mutuwa, wannan bai hana yawancin mutane su kafirce ba.

3. Abu ne mai kyau mutum ya yi yawo a bayan ƙasa, domin ya gane wa idonsa ayoyin Allah, ya kuma ɗauki darasi da izina daga gare su.

4. Zalunci yana ɗaya daga cikin abubuwan da suka jawo hallaka ga al'ummun da suka gabata.

5. Yin izgili da addini da hukunce-hukuncen shari’a kafirci ne.

6. Bayanin adalcin Allah wajen yi wa masu laifuka uƙuba.

Suratur Rum (8-10)

أَوَ لَمۡ يَتَفَكَّرُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۗ مَّا خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَأَجَلٖ مُّسَمًّىۗ وَإِنَّ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلنَّاسِ بِلِقَآيِٕ رَبِّهِمۡ لَكَٰفِرُونَ ٨ أَوَ لَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗ وَأَثَارُواْ ٱلۡأَرۡضَ وَعَمَرُوهَآ أَكۡثَرَ مِمَّا عَمَرُوهَا وَجَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٩ ثُمَّ كَانَ عَٰقِبَةَ ٱلَّذِينَ أَسَٰٓـُٔواْ ٱلسُّوٓأَىٰٓ أَن كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَكَانُواْ بِهَا يَسۡتَهۡزِءُونَ ١٠

8. Yanzu ba su yi tunani a kan kansu ba? Allah bai halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu ba sai da gaskiya kuma (ya yi su zuwa) lokaci ƙayyadajje. Lalle mafi yawan mutane masu kafircewa ne da haɗuwa da Ubangijinsu.

9. Shin ba za su yi tafiya a bayan ƙasa ba su ga yadda ƙarshen waɗanda suka gabace su ya zama? Sun kasance sun fi su tsananin ƙarfi, sun kuma tona ƙasa suka kuma raya ta fiye da yadda su (mutanen Makka) suka raya ta, kuma manzanninsu sun zo musu da (ayoyi) bayyanannu; to Allah bai kasance Mai zaluntar su ba, sai dai su ne suka kansance suna zaluntar kawunansu.

10. Sannan kuma ƙarshen waɗanda suka munana (ayyukansu) ya kasance mummunan (sakamako), don sun ƙaryata ayoyin Allah, kuma sun kasance suna yin izgili gare su.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin mushirikai cewa me zai hana su nutsuwa su yi tunani a kan kawunansu, su ga irin halittar da ya yi musu, ya daidaita musu ita ta hanya mai ban mamaki, sannan su fahimci cewa Allah bai halicci sammai da ƙasa don wasa ba, ya halicce su ne da gaskiya don a bauta masa shi kaɗai, ya kuma sanya musu ƙayyadajjen lokaci na wanzuwarsu a duniya; idan lokacin gushewarsu ya yi Allah zai tafiyar da su ya canja su da wasu domin yin hisabi.
Sai kuma Allah ya nuna cewa yawancin mutane suna kafirce wa haɗuwarsu da Ubangijinsu ranar alƙiyama, wannan ne ya hana su yin wani kazar-kazar domin tanadin zuwan wannan rana ta hanyar yin imani da ayyuka nagari.
Sai kuma Allah ya bayyana cewa, me ya sa su waɗannan masu ƙaryata Manzonsa (ﷺ) ba za su yi yawo a ƙasashen duniya ba, domin su samo darussa na al'ummun da suka gabace su waɗanda suka ƙaryata annabawansu, su ga yadda ƙarshensu ya zama. Allah ya bayyana musu cewa waɗancan al'ummun da aka yi a baya sun fi su tsananin ƙarfi na jiki, domin mutane ne da suka tona ƙasa suka yi noma da gine-gine a kanta, suka raya ta da abubuwan more rayuwa fiye da yadda su mushirikai masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) suka yi. Amma kuma yayin da manzanninsu suka zo musu da hujjoji bayyanannu masu nuna Kaɗaitakar Allah sai suka ƙaryata su, sai ko Allah ya hallaka su, ya kuma tabbatar musu da cewa bai zalunce su da komai ba, su ne dai suka zalunci kawunansu ta hanyar kafirce wa Allah da manzanninsa da aikata ayyuka na saɓon Allah.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ƙarshen dai mutanen da suka munana ayyukansu da aikata shirka da saɓon Allah ƙarshe ne da ya yi matuƙar muni a gare su, saboda sun ƙaryata ayoyin Allah sun riƙa izgili da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da aƙidar tashi bayan mutuwa da ƙwararan dalilai tare da tabbatar da sakamakon ayyuka.

2. Tabbatar da cewa mushriki ko kafiri ba zai samu ceto ba a ranar alƙiyama, da rushe aƙidar masu ganin ababen tarayyarsu da Allah za su cece su a wannan ranar.

3. Tabbatar da kasuwar halittu a ranar alƙiyama gida biyu, 'yan Aljanna masu samun ni'ima ta har abada, da kuma 'yan wuta masu dawwama a cikinta har abada.
Wannan ita ce rabuwar da babu haɗuwa a cikinta har abada.

Suratur Rum (11-16)
ٱللَّهُ يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ ثُمَّ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ١١ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يُبۡلِسُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ١٢ وَلَمۡ يَكُن لَّهُم مِّن شُرَكَآئِهِمۡ شُفَعَٰٓؤُاْ وَكَانُواْ بِشُرَكَآئِهِمۡ كَٰفِرِينَ١٣ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يَوۡمَئِذٖ يَتَفَرَّقُونَ١٤ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَهُمۡ فِي رَوۡضَةٖ يُحۡبَرُونَ١٥ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَلِقَآءِ ٱلۡأٓخِرَةِ فَأُوْلَٰٓئِكَ فِي ٱلۡعَذَابِ مُحۡضَرُونَ١٦

11. Allah ne Yake farar halitta sannan Ya dawo da ita (bayan mutuwa), sannan kuma gare Shi za a komar da ku.

12. Kuma ranar da alƙiyama za ta tashi, a wannan ranar ne masu manyan laifuka (kafirai) za su yanke ƙauna daga rahama.

13. Daga abokan tarayyar tasu kuwa ba su da wasu masu ceton su, za su ma kasance masu kafirce wa abokan tarayyar tasu.

14. Kuma ranar da alƙiyama za ta tashi, a wannan ranar ne (mutane) za su rarrabu.

15. To amma waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to su kam suna cikin dausayin (Aljanna) ana faranta musu rai.

16. Amma kuma waɗanda suka kafirta suka kuma ƙaryata ayoyinmu da haɗuwa da ranar lahira, to waɗannan za a halartar da su cikin azaba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da kawo dalilai masu tabbatar da tashin alƙiyama wanda mushirikai suke ƙaryatawa. Allah ya bayyana cewa shi ne mai ƙirƙirar halitta ba tare da ya gani a wurin wani ya kwaikwaya ba, sannan zai kashe abin da ya halitta idan lokacin mutuwarsa ya zo, sannan zai sake dawo da shi da ransa, sannan zuwa wajensa ne za a mayar da kowa domin yin hisabi da sakamakon ayyuka a ranar alƙiyama.
Sai kuma Allah ya bayyana halin da kowa zai tsinci kansa a ciki a wannan ranar da cewa, masu manyan laifuka, watau kafirai, za su fitar da tsammanin samun rahamar Allah, domin a ranar duk wata hujjarsu ta yin kafirci za ta zo ƙarshe, kuma daga duk gumakan da suka riƙa bautar su a nan duniya tare da Allah su rasa samun waɗanda za su cece su daga azabar Allah kamar yadda suke riyawa a duniya, sai ma a wannan rana za su zamanto masu kafirce musu ne, su nesantar da kansu daga shirkar da suka yi wa Allah da su, domin dukkansu za su yi tarayya cikin hallaka.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana rarrabuwar mutane kashi biyu a ranar.
Kashi na farko, su ne muminai waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to waɗannan za a saka su gidajen Aljanna a kuma yi ta faranta musu rai ta hanyar tanadar musu ni'ima ta har abada ba mai yankewa ba.
Kashi na biyu, su ne waɗanda suka kafirce wa Allah suka kuma ƙaryata ayoyin da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ), suka kuma ƙaryata tashi bayan mutuwa da ranar hisabi, to waɗannan su ne za a jefa su cikin azabar wutar Jahannama inda za su yi ta zama har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bawa ya zamanto mai raya lokutansa da salla da tasbihi wata alama ce da ke nuna kyakkyawan ƙarshe.

2. Kafa ƙwaƙƙwaran dalili a kan yiwuwar sake dawo da rai bayan mutuwa.

3. Bayanin lokutan sallolin farilla biyar.

4. Umarnin da Allah ya ba wa bayinsa muminai na su riƙa yi masa tasbihi a kowane lokaci, ya ƙunshi tasbihin da ya zamanto wajibi kamar wanda sallolin farilla suka ƙunsa da na mustahabbi kamar zikirori na safe da yamma da na bayan salloli da na nafilfilu. Domin waɗannan lokuta da Allah ya zaɓa su ne mafifitan lokuta a falala, don haka yawaita tasbihi da yabo ga Allah yake da matuƙar lada a cikinsu.

5. Ga duk wani mai hankali zai gane cewa Allah wanda yake raya ƙasa bayan mutuwarta, lalle zai iya dawo wa da matacce ransa bayan mutuwarsa. Babu dalilin da zai hana mai hankali ya yarda da wannan matuƙar dai ya amince da na farko.

Suratur Rum (17-19)

فَسُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ حِينَ تُمۡسُونَ وَحِينَ تُصۡبِحُونَ ١٧ وَلَهُ ٱلۡحَمۡدُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَعَشِيّٗا وَحِينَ تُظۡهِرُونَ ١٨ يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَيُخۡرِجُ ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّ وَيُحۡيِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَاۚ وَكَذَٰلِكَ تُخۡرَجُونَ ١٩

17. To tsarki ya tabbata ga Allah yayin kuka shiga lokacin maraice, da kuma yayin da kuka wayi gari.

18. Yabo kuma nasa ne a cikin sammai da ƙasa, da kuma yayin da kuka yi yammaci da kuma shigowarku lokacin azahar.

19. Yana fitar da rayayye daga matacce, Yana kuma fitar da matacce daga rayayye, kuma Yana raya ƙasa bayan mutuwarta. Kamar haka ne ku ma za a fito da ku (daga ƙaburburanku).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da tsarkakarsa daga duk wata tawaya ko wani aibi ko nakasa, kuma babu wani abu mai kama da shi a cikin halittunsa kakaf, don haka ya umarci bayinsa da su yi masa tasbihi, su tsarkake shi yayin da suka shiga lokacin maraice, watau lokutan sallar magariba da isha'i. Hakanan su yi masa tasbihi su tsarkake shi lokacin da suka wayi gari, watau lokacin sallar asuba.
Sannan ya tabbatar wa da kansa dukkan siffofin yabo da kirari, a sammai mala'iku suna yabon sa, a ƙasa kuma sauran halittunsa suna yabon sa.
Sai kuma ya umarci bayinsa da su yi masa tasbihi, su tsarkake shi yayin da suka shiga yammaci, watau lokacin sallar magariba da isha'i, da kuma yayin shigarsu lokacin asuba, watau sallar asuba.
Kuma ya bayyana cewa shi ne kaɗai wanda cikakke yabo da kirari ya tabbata a gare shi a cikin sammai da ƙasa. Duk halittunsa suna gode masa tare da yabon sa, don haka ya umarci bayaninsa su tsarkake shi lokacin shigar marece, watau sallar la'asar, su kuma tsarkake shi lokacin azahar, watau lokacin sallar azahar.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikakkiyar Kudurarsa da ikonsa, ta fitar da rayayye daga matacce, kamar fito da mutum daga ɗigon maniyyi, da fitar da ɗan tsako daga ƙwan kaza. Hakanan yake fitar da matacce daga cikin rayayye, kamar fitar da maniyyi daga mutum ko fitar da ƙwai daga kaza. Shi ne kuma mai raya ƙasa bayan ta bushe saboda rashin ruwa, sai ya saukar mata da ruwa daga nan sai ta fitar da tsirranta. To wannan cikakkiyar Kudura ta Allah ita take tabbatar da cewa zai fito da matattu daga ƙaburburansu bayan mutuwa domin yi musu hisabi a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dalilai masu nuna cikar Kudurar Allah da ya sanya a halittar ɗan'adam da kuma cikin sasannin sammai da ƙasa ayoyi ne da babu mai riskar su sai wanda ya yi amfani da hanyoyin tunani da karatun ta-nutsu da Allah ya hore masa.

2. Cikin hikimar Allah da ikonsa sai ya halicci ma'aurata daga jinsi ɗaya domin a samu nutsuwa da daidaito a tsakaninsu. Da a ce duk 'yan'adam maza ne, sannan ya halitta musu mata daga wani jinsi daban kamar aljannu ko dabbobi, to da ba a samu irin wannan nutsuwa ba.

3. Yana daga cikin rahamarsa yayin da ya shar'anta aure a Musulunci, kuma ya zama wani abu ne da zai jawo sabubban soyayya da tausayi tsakanin ma'aurata. Namiji zai kula da matarsa saboda soyayyar da take tsakaninsu da daɗin mu'amalar aure da yake samu daga wajenta, sannan su sami 'ya'ya tare, waɗanda za su ɗebe musu kewa.

4. Aure tsakanin 'yan'adam yana tattare da ayoyi daban-daban, daga cikinsu akwai:
a) Sanya wa ɗan'adam ƙa'idar rayuwa ta hanyar hayayyafa, aka kuma sanya wannan hayayyafar ta hanyar auratayya tsakanin namiji da mace, ba kamar irin hayayyafa ta tsirrai masu hayayyafa su kaɗai ba.
b) Sanya abokan auratayya na ɗan'adam su zama daga jinsinsa ba daga wani jinsi daban ba.
c) Sanya nutsuwa a tsakanin ma'aurata ba irin auratayya ta kwaɗi ba wadda take gudana cikin tsanani wani lokaci ma har abin ya kai ga hallaka.
d) Sanya ƙauna da soyayya a tsakanin ma'aurata. Da farko kafin su yi aure tana yiwuwa ɗaya bai san ɗayan ba, amma da zarar aure ya haɗa su sai ka ga an sami soyayya da ƙaunar juna a tsakaninsu kamar tun farko tare suka taso.
e) Sanya tausayi a tsakaninsu, har su wayi gari suna tausaya wa juna kamar tausayi na iyaye ga 'ya'yansu.
f) Saboda waɗannan ayoyi ne masu yawa da suke cikin sha'anin aure Allah ya rufe ayar da faɗarsa: "Lalle game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu tunani."

Suratur Rum (20-21)

وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنْ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ إِذَآ أَنتُم بَشَرٌ تَنتَشِرُونَ ﴿٢٠﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنْ خَلَقَ لَكُم مِّنْ أَنفُسِكُمْ أَزْوَٰجًا لِّتَسْكُنُوٓا۟ إِلَيْهَا وَجَعَلَ بَيْنَكُم مَّوَدَّةً وَرَحْمَةً ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿٢١﴾

20. Yana daga ayoyinsa cewa Ya halicce ku daga turɓaya, sannan kuma sai ga ku mutane kun warwatsu (a ko'ina).

21. Yana kuma daga ayoyinsa cewa Ya halitta muku mata daga jinsinku don ku samu nutsuwa gare su, Ya kuma sanya soyayya da jin ƙai tsakaninku. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu tunani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu manyan dalilai masu tabbatar da cikar Kudurarsa da cancantar ɗayanta shi da bauta, da kuma tashi bayan mutuwa.
Na farko, halittar mutum ta farko daga yumɓu, yayin da ya halicci asalin ubansu Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga yumɓu. Sai kuma daga nan mutane suka ci gaba da yaɗuwa ta hanyar hayayyafa, suka kuma warwatsu a ko'ina a bayan ƙasa.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah Ta'ala ya halicci Adamu daga damƙa ta ƙasa da ya ɗebo ta daga dukkanin dangogin ƙasa, sai 'ya'yan Adamu suka zo gwargwadon launukan wannan ƙasar, daga cikinsu akwai ja akwai fari akwai baƙi akwai tsaka-tsaki; akwai mai sauƙin kai akwai kuma mai wuyar sha'ani; akwai nagari akwai kuma mugu." [Abu Dawud #4693 da Tirmizi #2955].

Wannan aya ce mai nuna cewa wanda ya halicce ku daga asali guda, watau turɓaya, sannan ya yaɗa ku ko'ina a bayan ƙasa shi ne Ubangiji Ɗaya wanda zai iya dawo da ku bayan mutuwa.
Na biyu, halitta wa maza matansu na aure daga jinsinsu domin su samu nutsuwa da junansu, sannan ya sanya soyayya da tausayi a tsakaninsu. Allah ya tabbatar da cewa lalle a cikin wannan aiki nasa akwai dalilai bayyanannu ga mutane masu tunani masu amfani da hankalin da Allah ya ba su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittar sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu yana nuna girman iko da cikar ƙudurar wanda ya samar da su, yana kuma nuna yalwar iliminsa da hikimarsa da halittarsa, domin dole ne mahalicci ya san duk abin da ya halitta. Hakanan waɗannan halittu suna nuna gamammiyar rahamarsa saboda sun ƙunshi abubuwa manya-manya masu matuƙar amfani ga sauran halittunsa. Don haka wannan yana nuna shi Ɗaya ne tilo wanda ya cancanta a bauta masa, kar a haɗa shi da wani a bauta.

2. Daga cikin ayoyin Allah akwai sassaɓawar harsuna da launuka tare da yawansu da bambance-bambancensu, duk kuwa da cewa tushensu guda ɗaya ne, watau daga Adamu da Hauwa'u, sannan duk mafitar haruffansu iri ɗaya ne. Ba za ka taɓa samun mutane biyu ba waɗanda suka yi kama da juna ta kowace fuska. Lalle idan ka nutsu ka dube su sai ka ga abin da zai bambanta maka su.
Wannan lalle yana nuna cikar Kudurarsa da rahamarsa ga bayinsa, domin ba don waɗannan bambance-bambance da ke tsakaninsu ba da al'amuransu da dama sun rikice musu, sun kuma kasa cim ma manufofi da dama.

3. Yanayin barci ga ɗan'adam da dabba wani yanayi ne mai ban mamaki. Allah ya sanya wa jijiyoyin ƙwaƙwalwar ɗan'adam wani tsari wanda yake taimaka wa jiki da ƙwaƙwalwar ɗan'adam su dawo da nishaɗinsu da walwalarsu bayan sun yi aiki sun gaji. Sai Allah ya dakatar da aikin ƙwaƙwalwa ba tare da sauran gaɓoɓi manya na jiki sun dakata da aiki ba; Allah zai dakatar da aikin ƙwaƙwalwa na wani ɗan lokaci ne gwargwadon yadda nishaɗin mutum da ƙarfinsa za su dawo, sai ya farka daga barci ya ji shi garau.

4. Tabbatar da cewa masu amfani da hankulansu da jinsu su ne kaɗai masu yin imani.

Suratur Rum (22-23)

وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦ خَلْقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَٱخْتِلَٰفُ أَلْسِنَتِكُمْ وَأَلْوَٰنِكُمْ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّلْعَٰلِمِينَ ﴿٢٢﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦ مَنَامُكُم بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَٱبْتِغَآؤُكُم مِّن فَضْلِهِۦٓ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَسْمَعُونَ ﴿٢٣﴾

22. Yana kuma daga cikin ayoyinsa halittar sammai da ƙasa da kuma sassaɓawar harsunanku da launukanku. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga ma'abota ilimi.

23. Yana kuma daga cikin ayoyinsa baccinku da daddare da kuma rana da neman falalarsa da kuke yi. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga masu ji (na lura).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana ayoyinsa masu nuna cikakken ikonsa da Kaɗaitakarsa da Kudurarsa.
Na uku, akwai halittar sammai da ƙasa. Daga cikin abubuwan da Allah ya ajiye a bayan ƙasa kuma akwai 'yan'adam waɗanda ya yi su da harsuna iri-iri da launuka daban-daban, duk kuwa da kasancewarsu sun samo asali daga mutum guda ne, watau Annabi Adamu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa lalle a cikin wannan aiki nasa akwai ayoyi ga mutane masu ilimi da basira.
Na huɗu, barci da mutane suke yi da daddare ko da rana domin samun hutu daga wasu ayyukan gajiya. Hakanan akwai watsuwa da suke yi da rana domin neman arziki daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka); Allah ya tabbatar da cewa lalle a cikin wannan aiki nasa akwai hujjoji da dalilai ga mutane masu ji na lura da sauraro na fahimta da karɓa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saukar da ruwa daga sama yana nuna gamammiyar rahamar Allah ga bayinsa da cikar ikonsa da kamalar Kudurarsa a kan tayar da matattu bayan mutuwarsu.

2. Halittar sammai da ƙasa wata aya ce mai cin gashin kanta. Hakanan gudanarta a kan wani tsari guda ɗaya tun kafuwar duniya ba tare da samun wani canji ba, wannan ma wata ayar ce mai zaman kanta.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa da izininsa ne sammai da ƙasa suke tafiya a kan wannan tsari guda, don haka duk sanda ya ga dama zai iya tarwatsa wannan tsarin da kansa ya sake wani wanda yake so, kuma babu mai hana shi.

Suratur Rum (24-25)
وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ يُرِيكُمُ ٱلۡبَرۡقَ خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَيُنَزِّلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَيُحۡيِۦ بِهِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَآۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ٢٤ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَن تَقُومَ ٱلسَّمَآءُ وَٱلۡأَرۡضُ بِأَمۡرِهِۦۚ ثُمَّ إِذَا دَعَاكُمۡ دَعۡوَةٗ مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ إِذَآ أَنتُمۡ تَخۡرُجُونَ٢٥

24. Yana kuma daga cikin ayoyinsa nuna muku walƙiya da Yake yi don tsoratarwa da kwaɗaitarwa, Ya kuma saukar da ruwa daga sama, sai Ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane da suke hankalta.

25. Yana kuma daga cikin ayoyinsa sama da ƙasa su tsaya da umarninsa. Sannan kuma yayin da Ya kira ku (don ku tashi) daga ƙasa sai ga ku kuna fitowa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ambaton ayoyinsa masu nuna cikar Kudurarsa:
Na biyar, akwai walƙiya da yake nuna wa bayinsa gabanin saukar ruwan sama. Sai walƙiyar ta kasance tare da tsawa mai tsoratarwa, tare da sanya musu rai ga samun ruwan sama. Sai ko Allah ya saukar da ruwan sama wanda zai raya ƙasa bayan bushewarta ya fitar da tsirrai a kanta. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa lalle a cikin wannan aiki nasa akwai dalilai masu ƙarfi ga mutane masu hankali. Wannan ya isa ya zama hujja a kan yiwuwar tashi bayan mutuwa domin hisabi da sakamako.
Na shida, akwai tsayuwar sama ba tare da wani ginshiƙi da ya tokare ta ba ya hana ta faɗowa, da kuma tsayuwar ƙasa da izininsa (Mai tsarki da ɗaukaka) ba tare da tana tangal-tangal ba. To mai wannan Kudura da zai riƙe sammai da ƙasa da ita tabbas yana da iko idan ya kira halittarsa domin tashi daga ƙaburburansu sai kawai a gan su suna ta fitowa daga cikin ƙasa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk halittun Allah na sama da ƙasa masu ƙasƙantar da kansu ne ga Allah, sun so ko sun ƙi.

2. Duk wata siffa ta kamala ga wani mahaluki to mahalicci ne ya fi cancantar a jingina ta gare shi ta hanyar da babu wanda zai yi tarayya da shi a cikinta. Duk kuma wata siffa ta nakasa wadda za a tsarkake wani mahaluƙi daga ita, to Allah ne ya fi cancantar a tsarkake shi daga gare ta.

Suratur Rum (26-27)

وَلَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ كُلّٞ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ٢٦ وَهُوَ ٱلَّذِي يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَهُوَ أَهۡوَنُ عَلَيۡهِۚ وَلَهُ ٱلۡمَثَلُ ٱلۡأَعۡلَىٰ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٢٧

26. Kuma duk waɗanda suke cikin sammai da ƙasa nasa ne; dukkaninsu masu biyayya ne gare Shi.

27. Shi ne wanda Yake farar halittu, sannan Ya dawo da su (bayan mutuwa. Yin haka) kuwa shi ya fi sauƙi a gare Shi. Kuma siffofi mafiya ɗaukaka sun tabbata gare Shi a cikin sammai da ƙasa, kuma Shi ne Mabuwayi, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk abin da yake cikin sammai da ƙasa halittarsa ne, mulkinsa ne kuma bayinsa ne, dukkansu masu ƙaskantar da kai ne da miƙa wuya a gare shi.
Sai kuma ya ambaci cewa shi ne wanda ya ƙagi halitta ba tare da ya gani ya kwaikwaya ba, sannan shi ne zai dawo da abin da ya halitta bayan mutuwarsa, kuma dawo da shi ma ya fi sauƙi a gare shi a bisa ƙiyasin ɗan'adam, domin ƙagar abu daga babu ya fi maimaita yinsa a karo na biyu wuya, amma a wurin Allah duk ɗaya ne wajen sauƙi, domin shi idan yana nufin aikata wani abu cewa kawai yake da shi 'kasance', sai abin ya kasance.
Sai kuma Allah ya tabbatar da cewa shi ne wanda yake da siffofi mafiya ɗaukaka da kamala a sammai da ƙasa, shi kuma ne mabuwayi wanda ya fi ƙarfin kowa, kuma mai hikima ne a cikin duk ayyukansa.

An karɓo daga Abu Hurairah (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah yana cewa: "Ɗan'adam ya ƙaryata ni, bai kuma dace ya yi min haka ba. Ya kuma zage ni, bai kuma dace da shi ya yi min haka ba. Amma ƙaryatawar da ya yi mini cewarsa: 'Ba zai dawo da ni ba kamar yadda ya fare ni', alhalin ƙirƙirar halittar da farko ba ta fi min dawo da ita sauƙi ba. Amma zagi na kuwa da ya yi cewa da yake yi: 'Allah ya riƙi ɗa', alhalin ni ne Ɗaya tilo wanda ake nufi da buƙata, wanda bai haifa ba ba a kuma haife shi ba, kuma ba ya da wanda yake daidai da shi." [Bukhari #4974].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba da misali wajen koyarwa ko da'awa don matso da ma'anoni kusa da masu sauraro, wannan abu ne mai kyau kuma mai matuƙar amfani.

2. Misalan da Allah ya riƙa bayarwa a Alƙur'ani yana kawo su ne domin masu hankali, saboda su kaɗai ne za su fahimce su kuma su amfana da su.

3. Bin son zuciya da makauniyar biyayya ga iyaye da kakanni yakan hana mutum gane gaskiya ya bi ta.

4. Shiriya ta Allah ce, shi ne yake shiryar da wanda ya ga dama. Wanda Allah ya ɓatar da shi saboda ya cancanci ɓata, to babu mai iya shiryar da shi ko ya amfane shi a gaban Allah ranar alƙiyama.

Suratur Rum (28-29)

ضَرَبَ لَكُم مَّثَلًا مِّنْ أَنفُسِكُمْۖ هَل لَّكُم مِّن مَّا مَلَكَتْ أَيْمَٰنُكُم مِّن شُرَكَآءَ فِى مَا رَزَقْنَٰكُمْ فَأَنتُمْ فِيهِ سَوَآءٌ تَخَافُونَهُمْ كَخِيفَتِكُمْ أَنفُسَكُمْۚ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿٢٨﴾ بَلِ ٱتَّبَعَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ أَهْوَآءَهُم بِغَيْرِ عِلْمٍۖ فَمَن يَهْدِى مَنْ أَضَلَّ ٱللَّهُۖ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ﴿٢٩﴾

28. Ya ba ku misali daga kawunanku; shin kuna da wasu abokan tarayya daga bayinku da kuka mallaka a kan da abin da Muka arzuta ku (da shi), ku da su ku zama daidai kuke game da wannan; kuna ma jin tsoron su kamar yanda kuke tsoron junanku? Kamar haka Muke rarrabe ayoyin (filla-filla) ga mutanen da suke hankalta.

29. Ba haka ba ne, waɗanda suka yi zalunci dai sun bi son ransu ne ba tare da wani ilimi ba; to wane ne zai shiryar da wanda Allah Ya ɓatar? Kuma ba su da wasu mataimaka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin munin shirka ta hanyar amfani da rayuwar mushirikai don su yi tunani su gane munin aƙidar bautar wanin Allah.
Ya bayyana cewa, yanzu shin cikinsu su mushirikai za a iya samun waɗanda suka mallaki bayi da barori waɗanda za su yi tarayya da su a cikin dukiyoyinsu da duk abin da suka mallaka har bayin nan su riƙa sarrafa dukiyarsu yadda suke so ba tare da neman izininsu ba, har ta kai suna jin tsoron kada bayin nasu su kwashe musu duk abin da suka mallaka, kamar yadda idan ‘ya’ya sun haɗa tarayya ta dukiya da wasu ‘ya’yan suke jin tsoron junansu kada sashensu ya hau kan dukiyar sashe? Tabbas babu wani mushiriki da zai yarda da wannan ga kansa, to amma me ya sa suke riya cewa Allah mahaliccin talikai yana da wasu ababen tarayya daga cikin abin da ya halitta da kansa a matsayin bayinsa kuma mulkinsa? Me ya sa suka yarda da cewa waɗannan ababen tarayya da suka riƙa suna iya yin tasarrufi a cikin sha’anin Ubangiji kamar yadda yake yi? Babu shakka wannan misali ne Allah ya ba da shi domin kawo musu gaskiya kusa da hankulansu, ta yadda duk mai hankali zai gane.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mushirikai ba sun ɓata ne saboda rashin samun gamsasshiyar hujja a kan ɓacin abin da suke kai ba, a’a, sun saki gaskiya ne domin bin son zuciya da kuma makauniyar biyayya ga iyayensu waɗanda suka samu a kan ɓata.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa waɗannan mutane sun riga sun ɓata ba su da wani uzuri da za su kawo a gabansa. To shin ko akwai wani wanda zai iya shiryar da wanda Allah ya riga ya ɓatar? Babu shakka babu mai iya yin haka. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa a ranar alƙiyama ba su da wasu mataimaka da za su kare su dag azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni da tsantsanta addini ga Allah shi kaɗai, watau ikhlasi.

2. Addinin Musulunci shi ne addinin da ya dace da halittar ɗan’adam ta asali, watau (*fiɗira*).

3. An ambaci tsayar da fuska maimakon zuciya, domin duk inda zuciya ta karkata to fuska ma can take fuskanta; to daga nan kuma sai aikin gaɓɓai ya biyo baya.

4. Yi wa addini a-yaga sabga ce ta mushirikai. Daga cikinsu aka samu masu bautar gumaka, da masu bautar rana da wata, har da masu bautar taurari, wasu kuma suna bautar aljannu da mala’iku ko wasu salihai. Daga cikinsu aka samu karkatattun Yahudawa da Nasara. Amma shi addinin Allah ai guda ɗaya ne tak, shi ne tsantsanta bauta ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai.

5. Gargaɗin Musulmi a kan su guji rarrabuwa ƙungiya-ƙungiya, kowace ƙungiya ta riƙa ƙanƙame abin da ta tashi a kansa na gaskiya da na ƙarya. Yin haka kamanceceniya ne da mushirikai wajen yagalgala addini. Addini ɗaya ne, abin bauta ɗaya ne, Manzo kuma ɗaya ne. Yawancin al'amuran addini malamai sun haɗu a kansu. Allah kuma shi ne ya ƙulla 'yan'uwantaka ta imani a tsakanin muminai ya ɗaure ta tamau. To me zai sa duk a yi watsi da wannan a gina rarrabuwa a tsakanin Musulmi a kan wasu 'yan mas'aloli na saɓani waɗanda ba su fita daga cikin furu'a ba har ta kai ana jifan juna da ɓata, ana jan layi a tsakanin juna. Wannan ba komai ba ne face ruɗun Shaiɗan da cim ma wata babbar manufarsa.

Suratur Rum (30-32)

فَأَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًا ۚ فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِى فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا ۚ لَا تَبْدِيلَ لِخَلْقِ ٱللَّهِ ۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٣٠﴾ مُنِيبِينَ إِلَيْهِ وَٱتَّقُوهُ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَلَا تَكُونُوا۟ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ﴿٣١﴾ مِنَ ٱلَّذِينَ فَرَّقُوا۟ دِينَهُمْ وَكَانُوا۟ شِيَعًا ۖ كُلُّ حِزْبٍۭ بِمَا لَدَيْهِمْ فَرِحُونَ ﴿٣٢﴾

30. To sai ka tsayar da fuskarka ga addini mai kauce wa ɓarna. (Shi ne) asalin halittar da Allah Ya halicci mutane a kanta. Ba wani canji ga halittar Allah. Wannan shi ne miƙaƙƙen addinin, sai dai kuma yawancin mutane ba su san (haka ba).

31. Kuma kuna masu komawa zuwa gare Shi (wato Allah) kuma ku kiyaye dokokinsa ku kuma tsai da salla kuma kada ku zamanto cikin mushirikai.

32. Irin waɗanda suka rarraba addininsu suka kuma zamanto ƙungiya-ƙungiya; kowacce ƙungiya tana mai farin ciki da abin da yake nata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ma duk wanda ya yi imani da shi cewa ya tsayar da fuskarsa kyam ga addini miƙaƙƙe wanda ya ɗora shi a kansa ya umarce shi da ya bi shi, yana mai karkace wa duk wasu gurɓatattun addinai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa Musulunci shi ne addinin da ya dace da halittar Allah ta asali wadda ya halicci mutane a kanta, kuma babu wani canji ga halittar tasa. Sai ya sake tabbatar masa da cewa wannan umarni da ya ba shi shi ne addini miƙaƙƙe wanda babu karkata a cikinsa, sai dai yawancin mutane ba su san haka ba.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: 'Babu wani yaro da za a haifa sai a kan halittarsa ta asali (watau *fiɗira*) sai dai daga baya ne iyayensa suke mayar da shi Bayahude ko su mayar da shi Banasare ko Bamajuse. Kamar yadda ake haifar dabba mai cikakkiyar halitta, shin kukan gan ta da yagaggen kunne?" Sannan sai Manzon Allah (ﷺ) ya karanta wannan ayar." [Bukhari #4775 da Muslim #2658].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su koma ga Allah tare da yin tuba daga zunubbansu su kuma kiyaye dokokinsa ta hanyar aikata abin da ya wajabta musu da guje wa abin da ya haramta musu, kuma su tsayar da salla kamar yadda ya dace. Ya kuma gargaɗe su da kada su kasance daga cikin mushirikai waɗanda suka gurɓata halittunsu na asal,i suka haɗa Allah da wasu a wajen bauta, ko kuma su zama cikin mushirikai waɗanda suka yi wa addininsu a-yaga, watau suka yi imani da wani sashe nasa suka kafirce wa wani sashe, sai suka rarraba ƙungiya-kungiya, kowace ƙungiya suna farin ciki da ɓarnar da suke kai, domin suna ganin su kaɗai ne a kan gaskiya, duk sauran a kan ɓata suke.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani ɗan’adam da ba zai koma ga Allah ya roƙe shi ya tsantsanta addu’arsa gare shi ba sai lokacin da ya shiga halin matsuwa da tsanani, amma idan Allah ya yaye masa masifarsa sai ya watsar da shi, to wannan komawar tasa ba mai amfani ba ce, kuma talala ce Allah yake yi masa, duk sanda ya damƙe shi ba zai ji da daɗi ba.

2. Butulce wa ni’imar Allah ɗabi’a ce ta mushirikai.

3. Abin da kafirai suke ciki na yalwar ni’imomin Allah a gare su ba komai ba ne face talala da Allah yake yi musu.

4. Farin cikin girman kai yayin da wani ya sami wata ni’ima, ko ɗebe ƙauna daga samun rahamar Allah waɗannan siffofi ne na kafirai.

Suratur Rum (33-37)

وَإِذَا مَسَّ ٱلنَّاسَ ضُرٌّ دَعَوْا۟ رَبَّهُم مُّنِيبِينَ إِلَيْهِ ثُمَّ إِذَآ أَذَاقَهُم مِّنْهُ رَحْمَةً إِذَا فَرِيقٌ مِّنْهُم بِرَبِّهِمْ يُشْرِكُونَ ﴿٣٣﴾ لِيَكْفُرُوا۟ بِمَآ ءَاتَيْنَٰهُمْ ۚ فَتَمَتَّعُوا۟ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿٣٤﴾ أَمْ أَنزَلْنَا عَلَيْهِمْ سُلْطَٰنًا فَهُوَ يَتَكَلَّمُ بِمَا كَانُوا۟ بِهِۦ يُشْرِكُونَ ﴿٣٥﴾ وَإِذَآ أَذَقْنَا ٱلنَّاسَ رَحْمَةً فَرِحُوا۟ بِهَا ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌۢ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ إِذَا هُمْ يَقْنَطُونَ ﴿٣٦﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ﴿٣٧﴾

33. Idan kuma wani matsi ya sami mutane sai su roƙi Ubangijinsu suna masu komawa gare Shi, sannan kuma idan Ya ɗanɗana musu rahama daga gare Shi sai ka ga wata ƙungiyar daga cikinsu suna tarayya da Ubangijinsu.

34. Don su kafirce wa abin da Muka ba su. To ku ji daɗi, da sannu za ku sani.

35. Ko kuma Mun saukar musu da wani littafi ne wanda shi ne yake magana da abin da suka kasance suna shirka da shi?

36. Idan kuma Muka ɗanɗana wa mutane rahama sai su yi farin ciki da ita; idan kuwa wata masifa ta same su saboda abin da hannayensu suka gabatar sai ka gan su suna ɗebe ƙauna.

37. Yanzu ba su gani ba cewa Allah Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, Yana kuma ƙuntatawa (ga wanda ya ga dama)? Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suke yin imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin wasu mutane mushirikai masu butulce wa ni’imomin da yake yi musu a kai-a kai, da cewa akwai wasu mutane waɗanda idan wani tsanani ya same su, kamar rashin lafiya ko talauci ko fari, sai su marairaice wa Allah suna roƙon sa shi kaɗai domin ya yaye musu masifarsu. Sai idan ya ji ƙan su ya raba su da masifar da suke ciki, sai kawai a samu wasu daga cikinsu sun koma sun ci gaba da shirkar da suke yi wa Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wannan hali nasu shi ne ya kai su ga kafirce wa ni’imomin da ya ba su, don haka ya yi musu talala da cewa su ci gaba da jin daɗin rayuwarsu ta duniya, da sannu za su gani da idanunsu a ranar alƙiyama su tabbatar da cewa sun kasance a kan ɓata mabayyani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci mushirikai a kan hujjarsu ta yin shirka da shi. Shin ya saukar musu da wani littafi ne wanda suke kafa hujja da shi a kan shirkarsu? Ba shakka a fili yake

cewa babu wani littafi saukakke tare da su wanda yake goyon bayan shirkar da suke yi da Allah, ko wani aikin kafirci ko na saɓo.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wata mummunar ɗabi'a ta mutane, sai dai waɗanda Allah ya tsare, da cewa idan ya ba su wata ni'ima daga cikin ni'imominsa, kamar lafiya ko arziki sai su riƙa farin ciki na girman kai da wannan ni'imar, amma idan wani mummunan abu ne ya same su, kamar rashin lafiya ko talauci sakamakon laifuffukansu, sai kawai a gan su suna ɗebe ƙauna daga samun rahamar Allah, ko su fitar da rai cewa Allah zai iya yaye musu abin da yake damun su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jawo hankalinsu da cewa, yanzu ba sa ganin Allah ne yake yalwata arzikinsa ga wanda ya ga dama daga bayinsa don ya jarrabe shi ya ga ko zai gode masa ko kuma zai butulce masa? Yake kuma ƙuntata wa wanda ya ga dama daga cikinsu don ya jarrabe shi ya ga ko zai yi haƙuri ba zai yi raki ba? Allah ya tabbatar da cewa a cikin wannan aiki nasa lallai akwai ayoyi masu nuna cikar rahamarsa da luɗufinsa ga mutane muminai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni a kan taimaka wa ɗan'uwa makusanci da gwargwadon abin da Allah ya hore wa mutum.

2. Ba wa masu haƙƙi haƙƙoƙinsu wata hanya ce ta samun babban rabo a wurin Allah.

3. Allah yana cire albarka daga cikin dukiyar riba, yana kuma ninka lada ga wanda ya yi sadaka dominsa.

4. Matafiyin da guzuri ya ƙare masa yakan shiga matsuwa, don haka taimaka masa don ya isa garinsa wajibi ne a kan masu hali.

5. Rushe wata mummunar al'ada ta Larabawa a lokacin jahiliyya, wadda mutum yakan fifita taimaka wa wani na nesa a kan ɗan'uwansa makusanci ba don komai ba sai domin neman suna da shahara a bainar jama'a, sai Allah ya umarci Musulmi da su nisanci aikata haka.

6. Duk wani aikin alheri da amfaninsa zai kai ga wasu, to yana cike da alheri da falala mai yawa a wurin Allah.

7. Duk wanda ya bayar da sadaka ko kyauta da niyyar a mayar masa da fiye da abin da ya bayar, to ba shi da lada a wurin Allah.

Suratur Rum (38-40)
فَاتِ ذَا ٱلۡقُرۡبَىٰ حَقَّهُۥ وَٱلۡمِسۡكِينَ وَٱبۡنَ ٱلسَّبِيلِۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ لِّلَّذِينَ يُرِيدُونَ وَجۡهَ ٱللَّهِۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ٣٨ وَمَآ ءَاتَيۡتُم مِّن رِّبٗا لِّيَرۡبُوَاْ فِيٓ أَمۡوَٰلِ ٱلنَّاسِ فَلَا يَرۡبُواْ عِندَ ٱللَّهِۖ وَمَآ ءَاتَيۡتُم مِّن زَكَوٰةٖ تُرِيدُونَ وَجۡهَ ٱللَّهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُضۡعِفُونَ ٣٩ ٱللَّهُ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ ثُمَّ رَزَقَكُمۡ ثُمَّ يُمِيتُكُمۡ ثُمَّ يُحۡيِيكُمۡۖ هَلۡ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَفۡعَلُ مِن ذَٰلِكُم مِّن شَيۡءٖۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٤٠

38. Sannan ka bai wa (ɗan'uwa) makusanci haƙƙinsa da miskini da matafiyi. Wannan shi ya fi alheri ga waɗanda suke nufin Fuskar Allah; kuma waɗannan su ne masu rabauta.

39. Kuma abin da kuka bayar na riba don ya ƙaru a cikin dukiyoyin mutane, to ba ya ƙaruwa a wurin Allah; abin kuma da kuka bayar na zakka kuna masu nufin Fuskar Allah, to waɗannan su ne masu ninninka (ladansu).

40. Allah (Shi ne) Wanda Ya halicce ku sannan Ya arzuta ku sannan Shi zai kashe ku sannan Ya raya ku; shin a cikin abokan tarayyarku akwai wanda zai aikata wani abu daga wannan? Tsarki ya tabbata a gare Shi, Ya kuma ɗaukaka daga abin da suke tarawa (da Shi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Musulmi da ya ba wa ɗan'uwansa makusanci haƙƙinsa yayin da yake cikin wata buƙata domin kyautata masa da kuma sada zumunci da ke tsakaninsu; da kuma miskini mabuƙaci shi ma ya ba shi abin da zai biya masa buƙatarsa gwargwadon halinsa. Hakanan ya taimaka wa matafiyin da guzurinsa ya yanke don ya sami abin da zai mayar da shi garinsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa irin wannan taimako da yake umarni da shi shi ne mafi alheri ga mutanen da suke fuskantar Allah don neman yardarsa, kuma masu ba da irin wannan taimako lalle su ne masu samun babban rabo, watau gidan Aljanna da kuɓuta daga azabar Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana aikin da wasu mutane suke yi ba don Allah ba sai don nufin tara abin duniya wanda ba zai kai su ko'ina ba. Irin wannan aiki shi ne bayar da dukiyarsu bashi ga wasu mutane don su dawo musu da ita tare da ƙari, watau kuɗin riba. To wannan aiki nasu ba zai ƙare su da komai ba a wurin Allah, sai dai ya rushe duk wata albarka daga cikin dukiyarsu, kuma ba su da wani lada a wurin Allah, domin aikinsu ya rasa ikhlasi wanda sharaɗi ne na karɓar ayyukan bayi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) Ya tabbatar da cewa duk wani abu da za su bayar na dukiyarsu don Allah ga wani, don ya yi maganin buƙatarsa, ba don neman wani matsayi ko yabo daga mutane ba, to waɗannan su ne ake riɓanya musu ladansu a wurin Allah.
Malaman tafsiri da dama daga cikin magabata da 'yan baya sun fassara wannan ayar da cewa, a nan Allah yana hana su bayar da kyauta ne don tsammanin a rama musu da mafi yawan abin da suka bayar. Ya nuna musu cewa irin wannan kyautar ba ta da lada a wurin Allah, domin ba don shi aka yi ta ba, an yi ta ne domin a sami ƙari. Sai kuma Allah ya bayyana musu irin kyautar da za su yi su sami ninkin ladanta a wurinsa, ita ce wadda za su yi dominsa shi kaɗai.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: 'Wanda ya yi sadaka da kwatankwacin ƙwayar dabinuwa ɗaya ta kuɗin halal, domin Allah ba ya karɓa sai abin da yake halal ne, to Allah zai karɓi (sadakarsa) da hannunsa na dama, sannan ya yi masa renonta kamar yadda ɗayanku yake renon ɗan duƙushin dokinsa, har sai ta koma kamar dutse babba." [Bukhari #1410 da Muslim #1014].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi kaɗai ne ya keɓanta da yin halitta da arzutawa da kashewa sannan da rayawa bayan mutuwa domin yin hisabi ranar alƙiyama. Ya tabbatar da cewa babu wani abu da masu shirka suke yin shirka da shi da zai iya yin ɗaya daga cikin waɗannan ayyukan, ko ya yi tarayya da shi a cikinsu. Sai kuma ya tsarkake kansa daga duk abin da suke yin shirka da shi. Abin da kuma suke yin shirka ba zai cutar da shi da komai ba sai dai su su cuci kawunansu.'

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yaɗuwar ɓarna da tabarɓarewar aƙidun mutane ta hanyar yin shirka da saɓon Allah, shi ne yake jawo yaɗuwar cututtuka da fari da talauci da annoba da yaƙe-yaƙe da fitintinu a cikin al'umma.

2. Allah wanda ya kaɗaita a ayyukansa na Rububiyya, kamar halitta da kashewa da rayawa da arzutawa, shi ne kaɗai wanda ya cancanta a kaɗaita shi da bauta.

3. Bayanin girman rahamar Allah da tausayawarsa ga bayinsa. Da a ce zai kama su da dukkan laifukansu to da babu wanda zai yi saura a bayan ƙasa. Amma sai ya zamanto yana kama su ne da wani sashe na laifukansu yana kuma yafe musu yawancin laifukansu.

4. Tafiya a bayan ƙasa don ɗaukar izina da wa’azi yakan kasance da gangar jiki, yakan kuma zamanto da zuciya, yayin da za ta yi nazarin abin da ya faru ga waɗanda suka gabata suka ƙaryata manzannin Allah, da yadda Allah ya hallaka su da azabarsa.

Suratur Rum (41-42)

ظَهَرَ ٱلۡفَسَادُ فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِ بِمَا كَسَبَتۡ أَيۡدِي ٱلنَّاسِ لِيُذِيقَهُم بَعۡضَ ٱلَّذِي عَمِلُواْ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٤١ قُلۡ سِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلُۚ كَانَ أَكۡثَرُهُم مُّشۡرِكِينَ ٤٢

41. Ɓarna ta bayyana a kan tudu da kuma (cikin) ruwa saboda abubuwan da hannayen mutane suka aikata don a ɗanɗana musu sashin abin da suka aikata, ko wataƙila sa juyo.

42. Ka ce (da su): “Ku yi tafiya mana a bayan ƙasa sannan ku duba ku ga yadda ƙarshen waɗanda suke gabaninku ya zama. Yawancinsu sun kasance mushirikai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ɓarna da fasadi suka bayyana a bayan ƙasa suka watsu a ko’ina, mutane da yawa kuma suna shirka da Allah, wasu suna zaluntar bayin Allah da aikata laifuffuka iri daban-daban, wanda hakan ya haifar da lalacewar rayuwa a tudu da ruwa, cututtuka suka yawaita a bainar jama’a, aka rasa samun zaman lafiya, sai yaƙe-yaƙe da fitintinu, duk kuwa wannan ‘yan’adam ne suka jawo wa kawunansu shi saboda munanan ayyukansu, domin Allah ya ɗanɗana musu wani sashi na sakamakon ayyukansu tun a nan duniya domin fatan su koma gare shi su tuba su gyara halayensu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Manzonsa (ﷺ) cewa ya umarci mushirikai su yi tafiya a bayan ƙasa don su gane wa idanuwansu yadda al’ummun da suka gabace su suka ƙaryata manzanninsu suka yi mummunan ƙarshe. Yawancinsu shirka suka yi wa Allah suna bautar wasu ba shi ba, sai ya hallaka su saboda hakan.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni da riƙo da addini a aikace wajen maganganu da wajen ayyuka.

2. Amfani da rayuwa da Allah ya ara wa bayinsa wajen yawaita ayyukan alheri tun kafin zuwan ranar alƙiyama wadda babu makawa sai ta zo. Duk wanda kuwa ya riga ya mutu to ƙaramar alƙiyamarsa ta tsaya don babu dawowa duniya a gare shi har abada.

3. Kowane rai shi ne ke da alhakin ayyukansa masu kyau da munana a ranar alƙiyama.

4. Bayanin cewa Allah ba ya son kafirai, don haka ni’imomin da yake ba su a duniya ba na soyayya ba ne, talala yake yi musu don ya kama su bisa hujja.

Suratur Rum (43-45)

فَأَقِمۡ وَجۡهَكَ لِلدِّينِ ٱلۡقَيِّمِ مِن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَ يَوۡمٞ لَّا مَرَدَّ لَهُۥ مِنَ ٱللَّهِۖ يَوۡمَئِذٖ يَصَّدَّعُونَ ٤٣ مَن كَفَرَ فَعَلَيۡهِ كُفۡرُهُۥۖ وَمَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا فَلِأَنفُسِهِمۡ يَمۡهَدُونَ ٤٤ لِيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِن فَضۡلِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٤٥

43. To sai ka tsai da fuskarka ga addini madaidaici tun kafin ranar nan da ba ta da makawa ta zo daga Allah; a wannan ranar ne (mutane) za su rarraba.

44. Wanda ya kafirta to zunubin kafircinsa yana kansa; waɗanda kuwa suka yi aiki kyakkyawa, to kansu suke yi wa shimfiɗa (ta alheri).
45. Don (Allah) Ya saka wa waɗanda suka yi imani suka yi ayyuka nagari daga falalarsa. Lalle Shi (Allah) ba Ya son kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya tsayar da fuskarsa kyam ga addinin Musulunci wanda yake miƙaƙke ne babu wata karkata a cikinsa, ta hanyar tsantsanta bauta ga Allah da bin umarninsa da guje wa haninsa a zahiri da baɗini cikin rayuwarsa ta nan duniya tun gabanin zuwan ranar da ba ta da makawa daga Allah, watau ranar alƙiyama wadda ba za a jinkirta wa mutane ba idan ta zo don su yi wani aiki, ba abin da zai kasance a ranar sai sakamako. A wannan ranar mutane za su rarrabu; wasu a nufi gidan Aljanna da su a sanya su cikin ni'imominta; wasu kuma a nufi gidan wutar Jahannama da su a jefa su cikin azabarta.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk abin da ya sami wani a wannan ranar to sakamakon aikinsa ne na nan duniya ya gani, don haka wanda ya kafirce wa Allah kansa ya cuta, domin zai dawwama ne a cikin wutar Jahannama; wanda kuwa ya yi kyakkyawan aiki don Allah, to shi ma kansa yake yi wa shimfiɗa ta alheri wadda za ta kai shi ga shiga Aljanna ya zauna a cikin ni'imominta har abada. Sai kuma ya bayyana dalilin rarrabuwarsu ƙungiyoyi biyu a lahira, da cewa ya yi haka ne domin ya saka wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari da kyakkyawan sakamako fiye da aikinsu. Su kuma waɗanda suka kafirce masa da manzanninsa Allah ya tabbatar da cewa ba ya son kafirai, don haka za su gamu da fushinsa da azabarsa a ranar alƙiyama.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa bayinsa ni'imomi ne domin su gode masa ta hanyar bauta masa shi kaɗai ba tare da sun haɗa shi da abokin tarayya ba, idan kuwa har suka butulce wa wannan ni'ima da ya yi musu to sai ya azabtar da su da abin da ya ga dama a sanda ya ga dama.

2. Yalwar ni'imomin Allah da gamewarsu ga kowa da kowa har ma ga waɗanda ba su yi imani da Allah ba.

Suratur Rum (46)
وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَن يُرْسِلَ ٱلرِّيَاحَ مُبَشِّرَٰتٍ وَلِيُذِيقَكُم مِّن رَّحْمَتِهِۦ وَلِتَجْرِىَ ٱلْفُلْكُ بِأَمْرِهِۦ وَلِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ﴿٤٦﴾

46. Yana kuma daga ayoyinsa cewa Yana aiko iska tana mai yin albishir (da ruwa) kuma don Ya ɗanɗana muku rahamarsa, don kuma jiragen ruwa su riƙa gudana da umarninsa, kuma don ku nema daga falalarsa ko kwa gode.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake bayanin cikar Kudurarsa da gamammiyar rahamarsa ga bayinsa, da cewa daga cikin manya-manyan ayoyinsa masu nuna cikar Kudurarsa da Kaɗaitakarsa shi ne yana aiko da iska mai yi wa bayinsa albishir na saukar ruwan sama, daga nan sai ya saukar musu da ruwa don ya ɗanɗana musu rahamarsa su sami yalwar ruwan sama amfanin gonakinsu ya yi kyau, don kuma jiragen ruwansu su riƙa gudana a kan koguna ɗauke da su da kayayyakinsu da izininsa, don kuma su nemi falalarsa ta hanyar yin kasuwanci a cikin ruwa. Duk Allah ya yi musu waɗannan abubuwa ne domin su gode masa, shi kuma ya ƙara musu.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ya yi wa muminai alƙawarin taimaka musu da ba su nasara a koyaushe, amma da sharaɗin su inganta imaninsu da shi.
2. Razanarwa ga mushirikan Kuraishawa waɗanda suka ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da cewa idan suka ci gaba da mummunan halinsu na ƙaryata shi, to su sani azabar Allah na iya auka musu kamar yadda ta auka wa kafiran da suka gabace su yayin da suka ƙaryata annabawansu.

Suratur Rum (47)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ رُسُلًا إِلَىٰ قَوۡمِهِمۡ فَجَآءُوهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَٱنتَقَمۡنَا مِنَ ٱلَّذِينَ أَجۡرَمُواْۖ وَكَانَ حَقًّا عَلَيۡنَا نَصۡرُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ٤٧

47. Haƙiƙa kuma Mun aiko wasu manzanni gabaninka zuwa ga mutanensu, sai suka zo musu da hujjoji bayyanannu, sai Muka azabtar da waɗanda suka kafirce, kuma taimakon muminai ya zama haƙƙi ne a kanmu.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ba yanzu ne ya fara aiko da manzo ba. Ya aiko da manzanni tun gabanin Manzo (ﷺ) zuwa ga al'ummunsu masu aikata shirka da kafirci a bayan ƙasa. Manzannin suka je musu da hujjoji da dalilai masu ƙarfi masu tabbatar da gaskiyarsu, to amma sai suka ƙaryata abin da manzanninsu suka je musu da shi, sai Allah ya saukar da azabarsa ga waɗanda suka kafirce masa suka ƙaryata manzanninsa, ya hallaka su baki ɗaya, ya kuma kuɓutar da manzanninsa da waɗanda suka yi imani daga hallaka. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa ya wajabta wa kansa taimakon waɗanda suka yi imani a koyaushe.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake haɗo da hadari a sama, sannan ya saukar da ruwa a inda ya ga dama. Wannan ɗaya ne daga cikin ɗimbin abubuwa masu nuna girman Kudurarsa da rahamarsa ga talikai.

2. Saukar da ruwan sama a kan ƙasar da ta riga ta bushe sannan da fito da tsirran cikinta babban dalili ne da yake tabbatar da yiwuwar tashi bayan mutuwa.

3. Bayanin halin kafiri yayin da yake cikin yalwa ko ya shiga cikin wani tsanani; idan yana cikin halin tsanani sai ya cire tsammaninsa daga rahamar Allah, idan kuwa ya shiga halin yalwa sai ya butulce masa.

Suratur Rum (48-51)

ٱللَّهُ ٱلَّذِي يُرۡسِلُ ٱلرِّيَٰحَ فَتُثِيرُ سَحَابٗا فَيَبۡسُطُهُۥ فِي ٱلسَّمَآءِ كَيۡفَ يَشَآءُ وَيَجۡعَلُهُۥ كِسَفٗا فَتَرَى ٱلۡوَدۡقَ يَخۡرُجُ مِنۡ خِلَٰلِهِۦۖ فَإِذَآ أَصَابَ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦٓ إِذَا هُمۡ يَسۡتَبۡشِرُونَ٤٨ وَإِن كَانُواْ مِن قَبۡلِ أَن يُنَزَّلَ عَلَيۡهِم مِّن قَبۡلِهِۦ لَمُبۡلِسِينَ٤٩ فَٱنظُرۡ إِلَىٰٓ ءَاثَٰرِ رَحۡمَتِ ٱللَّهِ كَيۡفَ يُحۡيِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَآۚ إِنَّ ذَٰلِكَ لَمُحۡيِ ٱلۡمَوۡتَىٰۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ٥٠ وَلَئِنۡ أَرۡسَلۡنَا رِيحٗا فَرَأَوۡهُ مُصۡفَرّٗا لَّظَلُّواْ مِنۢ بَعۡدِهِۦ يَكۡفُرُونَ٥١

48. Allah (Shi ne) wanda Yake aiko da iska sai ta motsa girgije, sai Ya shimfiɗa shi a (sararin) sama yadda Ya ga dama, Ya kuma sanya shi yanki-yanki, sai ka ga ruwa yana fitowa ta tsakaninsa, to idan Ya saukar da shi ga waɗanda Ya ga dama daga bayinsa sai ka gan su suna ta murna.

49. Ko da yake da can kafin a saukar musu shi tabbas sun kasance masu ɗebe ƙauna.

50. To sai ka yi duba ga guraben rahamar Allah (ka ga) yadda Yake raya ƙasa bayan mutuwarta. Lalle wannan tabbas Mai raya matattu ne, kuma Mai iko ne a kan komai.
51. Tabbas kuma in da za Mu aiko da iska su gan shi (wato amfanin gonarsu) ya yi fatsi-fatsi da sai su ci gaba da kafirce wa (Allah) bayan haka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana dalilai da hujjoji masu nuna Kudurarsa da ikonsa a kan tayar da matattu bayan mutuwa da kuma cikakkiyar rahamarsa da ta yalwaci komai, da cewa shi ne wanda yake aiko da iska iri daban-daban sai ta haɗo hadari sannan ta motsa shi, sai Allah ya shimfiɗa shi a sararin sama yadda ya ga dama, kaɗan ko mai yawa, sannan ya mayar da shi yanki-yanki, sai a riƙa ganin ruwa yana saukowa daga tsakaninsa; to duk waɗanda suka yi dace wannan ruwa ya sauka gare su da yardar Allah sai su cika da farin ciki game da rahamar Allah da ta sauka gare su, sai gonakinsu su yi kyau su sami abincinsu da na dabbobinsu da ruwan shansu da na dabbobinsu. Allah ya bayyana halin da suke ciki kafin saukar wannan ruwan, watau har sun kasance sun ɗebe ƙaunar saukarsa domin ganin ya yi jinkirin zuwa, don haka ganinsa ya saka su cikin farin ciki mai yawa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) cewa ya duba ya ga guraben saukar wannan ruwa ya ga yadda ya cika da rahamar Allah ga bayinsa, ta yadda yake raya ƙasa da dangogin tsirrai iri-iri bayan ƙeƙashewarta na wani tsawon lokaci. Allah ya tabbatar da cewa lalle wanda ya iya raya wannan ƙeƙasasshiyar ƙasa tabbas zai iya dawo da matattu da ransu bayan mutuwa, domin shi mai iko ne a kan komai babu abin da zai gagare shi.
kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara fito da butulcin masu kafirce wa ni'imomin Allah da mantawa da rahamar da yake yi musu. Ya rantse cewa da zai aiko wa da gonakinsu wata iska wadda za ta lalata musu shuke-shukensu su yi fatsi-fatsi su lalace bayan da farko sun yi kore shar, to da sun koma suna kafirce wa duk ni'imomin da ya yi musu a baya ba tare da sun duba yawan rahamarsa da ya yi musu ba a can baya, watau maimakon su gode masa a kan ni'imominsa da ya yi musu marasa iyaka, su kuma yi haƙuri su dogara gare shi idan wani abin ƙi ya same su daga baya, to amma sai suka juyar da al'amarin, ba su gode masa ba a can baya sannan kuma suka dawo suka butulce masa.
Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:
1. Bayanin cewa kafirai matattu ne, don haka ba sa ji ba sa gani. Muminai su ne rayayyu domin su ne masu ganin gaskiya su bi ta, kuma masu jin ta su ɗauka.
2. Masu imani da ayoyin Allah su ne waɗanda suke jin gaskiya su karɓe ta, domin su ne suka sallama komai nasu ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
3. Kimsa shiriya a cikin zukata yana hannun Allah ne shi kaɗai. Aikin Manzon Allah (ﷺ) shi ne bayanin gaskiya ga mutane.

Suratur Rum (52-53)
فَإِنَّكَ لَا تُسۡمِعُ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَلَا تُسۡمِعُ ٱلصُّمَّ ٱلدُّعَآءَ إِذَا وَلَّوۡاْ مُدۡبِرِينَ ٥٢ وَمَآ أَنتَ بِهَٰدِ ٱلۡعُمۡيِ عَن ضَلَٰلَتِهِمۡۖ إِن تُسۡمِعُ إِلَّا مَن يُؤۡمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُم مُّسۡلِمُونَ ٥٣

52. To lalle kai ba ka iya jiyar da matattu, kuma ba ka iya jiyar da kurame kira lokacin da suka juya suna masu ba da baya.

53. Kuma kai ba mai iya shiryar da makafi (wato ɓatattu) ba ne daga ɓatansu; ba waɗanda kake iya jiyarwa sai waɗanda suka yi imani da ayoyinmu don haka suna masu miƙa wuya.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ƙwararan dalilai da hujjoji masu nuna Kaɗaitakarsa da cikakkiyar Kudurarsa a kan tayar da matattu da tashin alƙiyama domin hisabi, babu abin da kafirai suke ƙara yi sai bijirewa da kafircewa, sai Allah ya nuna wa Manzonsa cewa waɗannan kafirai sun zama kamar matattu ne ko kurame. To kamar yadda ba zai iya jiyar da matattu ko ya jiyar da kurame ba, hakanan ba zai iya jiyar da waɗanda suka bijire suka ƙi yarda su amfana da hujjojin da ake kawo musu ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa waɗannan ɓatattun da suka ƙi bin hanyar shiriya madaidaiciya ba zai iya dawo da su kan hanya ba, domin sun riga sun makance ba sa ganin gaskiya.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin matakan halittar ɗan'adam. Allah ya fara halittarsa daga rauni, watau tun yana ɗigon maniyyi a cikin cikin mahaifiya inda ya bi wasu matakai daban-daban har ya zama cikakkiyar halitta mai rai, sannan aka haife shi jariri bai san komai ba kuma ba zai iya yi wa kansa komai ba. Sannan ya fara hankali har ya tasa ya zama saurayi, har ya kai matsayin cikarsa babban mutum mai cikakken ƙarfi, daga nan ya fara gangara a hankali, ƙarfinsa ya riƙa raguwa yayin da tsufa ya kama shi. Yana ƙara tsawon rai rauninsa yana ƙaruwa, har ya koma kamar jariri ta yadda ba zai iya yi wa kansa komai ba saboda tsananin tsufa. Babu shakka wannan hikima ce ta Allah, don ya nuna wa bawansa rauninsa, ya fahimci cewa ƙarfinsa zagaye yake da rauni biyu, daga farkonsa da kuma ƙarshensa; ya gane cewa shi a karan kansa mai tawaya ne, ba don Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafe shi ba da babu wani abu na ƙarfi da zai iya yi wa kansa. Da kuma a ce ƙarfin ɗan'adam ƙaruwa zai yi ta yi ba ya raguwa a tsawon rayuwarsa to da ya cika da ɗagawa da girman kai.

2. Yana daga cikin hikimar Allah da ya nuna wa bayinsa cikar Kudurarsa wadda ba ta yankewa; da ita yake halittar abubuwa ya kuma gudanar da su ba tare da gajiya ko rauni sun riske shi ba.

Suratur Rum (54)

۞ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَكُم مِّن ضَعْفٍ ثُمَّ جَعَلَ مِنۢ بَعْدِ ضَعْفٍ قُوَّةً ثُمَّ جَعَلَ مِنۢ بَعْدِ قُوَّةٍ ضَعْفًا وَشَيْبَةً ۚ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ ۚ وَهُوَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْقَدِيرُ ﴿٥٤﴾

54. Allah (Shi ne) Wanda Ya halicce ku daga rauni, sannan kuma Ya sanya ƙarfi bayan raunin, sannan kuma Ya sanya rauni da furfura bayan ƙarfi. Yana halittar abin da Ya ga dama; Shi ne kuwa Masani, Mai iko.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu daga cikin ayoyin da ke tattare da halittar ɗan'adam da matakai daban-daban da yake bi ta kansu a rayuwarsa, masu nuna cikar Kudurar Allah da yalwar iliminsa da hikimarsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi ne ya halicci mutane suka fara daga rauni, watau lokacin da suke jarirai, har zuwa girmansu, sannan ya ba su ƙarfi bayan rauni, watau lokacin da suka kai ganiyar ƙarfinsu, sannan ya sake sanya musu rauni bayan ƙarfinsu, watau lokacin da tsufa ya cim musu. Hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake halittar abin da ya ga dama, ya sanya masa rauni ko ya sanya masa ƙarfi, shi ne masanin komai, babu abin da yake ɓuya a gare shi, kuma mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gagararsa.

Daga wannaan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halayyar mushirikai ta yin ƙarya ba za ta canza ba ko da an je lahira, kamar yadda a nan duniya suka ƙaryata manzannin Allah da zuwan lahira, to hakanan ma a can lahira za su ƙaryata cewa sun zauna wani lokaci mai tsawo a duniya. Duk kuwa abin da mutum ya mutu a kai, to a kansa za a tashe shi.

2. Falalar masu ilimi da imani.

3. Duk wani hanzari da kafirai za su bayar a ranar alƙiyama ba zai amfane su ba. Idan suka ƙaryata cewa an tsayar musu da hujja a duniya ko kuma ba a ba su damar yin imani ba, sai ƙaryarsu ta bayyana da shaidar masu imani da ilimi da kuma shaidar hannayensu da ƙafafuwansu da fatunsu. Idan kuma sun nemi a sake ba su wata dama a karo na biyu a mayar da su duniya domin su yi imani su yi ayyuka nagari, nan ma ba za su sami wannan damar ba, domin lokacinta ya riga ya wuce.

Suratur Rum (55-57)
وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يُقۡسِمُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ مَا لَبِثُواْ غَيۡرَ سَاعَةٖۚ كَذَٰلِكَ كَانُواْ يُؤۡفَكُونَ ٥٥ وَقَالَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ وَٱلۡإِيمَٰنَ لَقَدۡ لَبِثۡتُمۡ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡبَعۡثِۖ فَهَٰذَا يَوۡمُ ٱلۡبَعۡثِ وَلَٰكِنَّكُمۡ كُنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ ٥٦ فَيَوۡمَئِذٖ لَّا يَنفَعُ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مَعۡذِرَتُهُمۡ وَلَا هُمۡ يُسۡتَعۡتَبُونَ ٥٧

55. Kuma a ranar da alƙiyama za ta tashi masu manyan laifuka za su rantse (kan) ba su zauna ba (a ƙaburburansu) fiye da sa’a ɗaya. Kamar haka suka kasance ana karkatar da su (daga gaskiya).

56. Waɗanda kuwa aka bai wa ilimi da imani sai suka ce: “Haƙiƙa kun zauna ne gwargwadon yadda Allah Ya rubuta muku a littafinsa har zuwa ranar tashi; to wannan kuma ita ce ranar tashin, sai dai kuma ku kun kasance ba ku san (haka) ba.”

57. To a wannan ranar waɗanda suka yi zalunci hanzarinsu ba zai amfane su ba, kuma ba za a nemi su kawo wani uzuri ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ƙwararan hujjoji a kan tashi bayan mutuwa domin hisabi, sai kuma ya bayyana wani abu da zai faru a ranar alƙiyama tsakanin kafirai masu ƙaryata ta da muminai waɗanda suka yi imani da zuwanta. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa ranar da alƙiyama za ta tsaya, masu manyan laifuka, watau kafirai, za su riƙa rantsuwa a kan cewa ba su zauna a ƙaburburansu ba sai wani ɗan lokaci kaɗan. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaryata su ya tabbatar da cewa, kamar yadda suka kasa gane tsawon lokacin zamansu a ƙaburburansu, hakanan suka kasance a duniya ana karkatar da su daga bin gaskiya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara da cewa, waɗanda Allah ya ba wa ilimi da imani za su mayar musu da martani da cewa lalle sun zauna gwargwadon abin da Allah ya riga ya rubuta musu za su zauna tun daga lokacin halittarsu har zuwa ranar da aka tashe su daga ƙaburburansu, watau ranar alƙiyama, kuma wannan ita ce ranar tashin da suka ƙaryata a duniya, ga ta sun gan ta da idanuwansu, to amma a da sun kasance ba su san haka ba don haka ne suka kafirce wa ranar.
Sai kuma Allah ya tabbatar musu da cewa a wannan ranar da zai tayar da halittu gaba ɗaya, domin hisabi da ba da sakamakon ayyuka, duk wani hanzari da azzalumai za su ƙirƙiro su faɗa ba zai amfane su ba, kuma ba za a ba su wata dama ta su tuba a karɓi tubansu ba, domin lokacinta ya riga ya wuce.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yanke wa kowa hanzari ta hanyar hujjojin da ya ambata a littafinsa Alƙur'ani, hujjoji masu bayanin gaskiya da ma'abotanta da kuma ƙarya da ma'abotanta.

2. Mafi munin halin da ɗan'adam zai tsinci kansa a ciki shi ne, lokacin da za a toshe masa zuciyarsa, shiriya ta ƙi shiga cikinta saboda yawan zunubbansa, har ya wayi gari ba ya gane komai, ba ya kuma fahimtar komai.

3. Wajabcin haƙuri da juriya game da wautar masu wauta.

4. Duk wani mumini mai hankali da yaƙini, to haƙuri ba zai yi masa wuya ba, saɓanin wanda ya rasa hankali da yaƙini, shi kam haƙuri zai yi masa wuya.

Suratur Rum (58-60)

وَلَقَدۡ ضَرَبۡنَا لِلنَّاسِ فِي هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٖۚ وَلَئِن جِئۡتَهُم بِـَٔايَةٖ لَّيَقُولَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا مُبۡطِلُونَ ٥٨ كَذَٰلِكَ يَطۡبَعُ ٱللَّهُ
عَلَىٰ قُلُوبِ ٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَ ٥٩ فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞۖ وَلَا يَسۡتَخِفَّنَّكَ ٱلَّذِينَ لَا يُوقِنُونَ ٦٠

58. Kuma haƙiƙa Mun ba wa mutane kowane irin misali a cikin wannan Alƙur'anin. Kuma tabbas idan da za ka zo musu da wata aya lallai da waɗanda suka kafirce sun ce: "Ai ku maɓarnata ne kawai."

59. Kamar haka ne Allah Yake toshe zukatan waɗanda ba sa sanin (gaskiya).
60. Sai ka yi haƙuri, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne; kada kuma waɗanda ba sa sakankancewa (da alƙiyama) su ingiza ka (har ka kasa haƙuri).

A waɗannan ayoyi na ƙarshen Surar, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa bayan ya bayyana duk wasu dalilai masu gamsarwa a kan Ɗayantakarsa da kuma tashin alƙiyama, duk da haka yawancin kafirai sun ci gaba da ƙaryatawa, don haka babu wani dalili ko hujja da ta yi saura wadda za su gani su yi imani. Allah kuma ya bayyana cewa ya buga wa mutane kowane irin misali a cikin Alƙur'ani domin su bambance tsakanin ƙarya da gaskiya, amma yawancinsu sun bijire mata, to da Manzon Allah (ﷺ) zai zo musu da wata ayar daban mai nuna gaskiyarsa, tabbas da sai sun faɗa masa shi da muminai cewa, ba a kan komai suke ba sai ƙarya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa yadda ya toshe zukatan waɗannan kafiran har suka kasa fahimtar gaskiya, to kamar haka ne yake toshe zukatan duk waɗanda ba su san cewa abin da ya zo da shi gaskiya ne ba.
Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi haƙuri a kan ƙaryata shi da mutanensa suke yi, ya tabbatar masa cewa alƙawarin da ya yi masa na samun nasara da kafuwa a bayan ƙasa gaskiya ne, kuma mai tabbata ne babu makawa. Ya kuma gargaɗe shi da cewa kada ya yarda waɗanda ba su sakankance da tashinsu ranar alƙiyama ba su ingiza shi ya kasa haƙuri, har ya nemi a gaggauto da abin da suke son a gaggauto musu da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman matsayin Alƙur'ani.

2. Duk abubuwan da Alƙur’ani ya ƙunsa cike suke da hikima; labaransa duk hikima ne, hakanan hukunce-hukuncensa duk cike suke da hikima.

3. Alƙur’ani shiriya ne da rahama. Duk wanda ya yi riƙo da Alƙur’ani to ya samu shiriya kuma ya dace da rahamar Allah duniya da lahira.

4. Masu kyautatawa ne suke amfana da shiriyar Alƙur’ani, duk sanda bawa ya ƙara ƙaimi wajen kyautata ayyukansa tsakaninsa da Allah to amfanuwarsa da Alƙur’ani za ta ƙaru

5. Bawa ba zai taɓa rabauta ba har sai ya tsayar da salla ya kuma fitar da zakkar dukiyarsa idan ya mallaki nisabin zakka kuma lokacinta ya zo.

6. Ishara a kan falalar salla da zakka, domin dukansu rukunai ne na addinin Musulunci. Salla na gaba da zakka shi ya sa aka gabatar da ambatonta duk kuwa da kasancewar amfanin zakka yana kaiwa har ga wasu.



31-Suratu Luƙman

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna '*Suratu Luƙman*' domin a cikinta ne aka ambaci sunansa, tana kuma magana a kan hikimar da Allah ya ba shi.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malaman tafsiri sun ambaci cewa ita Sura ce *Makkiyya* gaba ɗayanta. Wannan maganar ita ce ta fi rinjaye.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta hamsin da bakwai (57) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratus Saffat*' gabanin '*Suratu Saba'i*'.

4. Adadin ayoyinta:
Ayoyinta talatin da huɗu ne (34) a lissafin mutanen Sham da Basra da Kufa. Amma a lissafin mutanen Makka da Madina adadinsu talatin da uku ne (33).

5. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne jawo hankalin ɗan'adam cikin hikima zuwa ga fahimtar Kaɗaitakar mahaliccinsa Allah yayin da zai yi duba zuwa ga manya-manyan ayoyinsa a sammai da ƙasa masu tabbatar da cancantar ya bauta masa shi kaɗai ba tare da yana haɗa shi da komai ba.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Nuni a kan girman matsayin Alƙur'ani da zamantowarsa shiriya ga muminai.
• Nuna wautar wanda zai kama zantukan banza don ya ɓatar da mutane daga kan tafarki maidaidaici.
• Ambaton ƙissar Luƙmanu da hikimar da Allah ya ba shi tare da kawo wasu wasiyyoyinsa ga ɗansa.
• Tunatar da mushrikai wasu dalilai masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah da tuna musu wasu ni'imomi da ya yi musu, amma suka bijire wa shiriyarsa suka riƙe abin da suka gada na shirka daga iyayensu da kakanninsu.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da kwantar masa da hankali dangane da kafircin kafirai.
• Mayar da martani a kan masu jayayya game da Alƙur'ani.
• Surar ta rufe da gargaɗi a kan da'awar Shaiɗan da faɗakarwa a kan bokaye masu da'awar sun san gaibu.

Suratu Luƙman (1-5)
الٓمٓ ١ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡحَكِيمِ ٢ هُدٗى وَرَحۡمَةٗ لِّلۡمُحۡسِنِينَ ٣ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ يُوقِنُونَ ٤
أُوْلَٰٓئِكَ عَلَىٰ هُدٗى مِّن رَّبِّهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ALIF LAM MIM.

2. Waɗannan ayoyin littafi ne mai hikima.

3. Shiriya ne da rahama ga masu kyautatawa.

4. Waɗanda suke tsai da salla suke kuma ba da zakka alhali su kuma suna masu sakankancewa da ranar lahira.

5. Waɗannan suna kan shiriya daga Ubangijinsu; waɗannan su ne masu rabauta.

Surar ta buɗe da haruffa kamar yadda wasu surori a gabaninta suka buɗe da irin waɗannan haruffa. [Duba farkon *Suratul Baƙara* don ƙarin bayani a kansu].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗannan ayoyi da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) ayoyi ne na littafin Alƙur'ani wanda yake cike da hikima, kuma shiriya ne ga mutane masu kyautata ayyukansu da sauke haƙƙoƙinsu tsakaninsu da Allah da tsakaninsu da sauran mutane 'yan'uwansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta waɗannan bayi nasa da cewa su ne masu tsayar da salla yadda ya kamata; suna yin ta a lokutanta da kula da hukunce-hukunceta. Suna kuma fitar da zakka daga cikin dukiyoyinsu, suna ba da ita ga waɗanda suka cancanci su ba su. Sannan kuma sun sakankance da ranar lahira kuma sun yi imani da abin da zai wakana a cikinta na hisabi da kyakkyawan sakamako da mummuna. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa lalle masu waɗannan siffofi su ne suka tabbata a bisa shiriya ta Ubangijinsu, su ne kuma masu samun babban rabo, domin za su samu abin da suke nema na kyakkyawan sakamako, sannan za a tsare su daga duk wani abin ƙi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin sauraron duk wani abu da zai shagaltar ko ya kautar da bawa daga tafarki madaidaici.

2. Malamai sun kafa hujja da wannan ayar ta 6 a kan haramcin sauraron waƙe-waƙe na banza waɗanda suke tattare da abin da shari'a ta haramta, kamar kayan kaɗe-kaɗe, ko maganganun batsa ko saɓon Allah ko cin mutunci ga wasu ko wani da makamantan haka.

Amma idan waƙe ne wanda babu kaɗe-kaɗe a tare da shi, kuma ya ƙunshi kyawawan maganganu na hikima ko wa'azi ko ilimantarwa, wannan babu laifi a saurare shi, matuƙar ba zai shagaltar daga abin da yake wajibi ba.

3. Yin izgili da ayoyin Allah kafirci ne.

4. Duk wanda ya wulaƙanta ayoyin Allah a duniya to shi ma zai gamu da azabar wulaƙantarwa a lahira domin sakamako yakan zo daidai da jinsin aiki.

5. Girman kai rawanin tsiya ne mai hana karɓar gaskiya.

Suratu Lukman (6-7)

وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَشۡتَرِي لَهۡوَ ٱلۡحَدِيثِ لِيُضِلَّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ بِغَيۡرِ عِلۡمٖ وَيَتَّخِذَهَا هُزُوًاۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٞ مُّهِينٞ ٦ وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِ ءَايَٰتُنَا وَلَّىٰ مُسۡتَكۡبِرٗا كَأَن لَّمۡ يَسۡمَعۡهَا كَأَنَّ فِيٓ أُذُنَيۡهِ وَقۡرٗاۖ فَبَشِّرۡهُ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٧

6. Daga mutane kuma akwai wanda yake sayen zantuka na sharholiya don ya ɓatar (da mutane) daga hanyar Allah ba tare da wani ilimi ba, yana kuma riƙon ta abar yi wa izgili. (Irin) waɗannan azaba mai wulaƙantarwa ta tabbata gare su.

7. Idan kuma ana karanta masa ayoyinmu sai ya juya yana mai girman kai kamar bai ji su ba, kamar a ce akwai wani nauyi a cikin kunnuwansa; to ka yi masa albishir da azaba mai raɗaɗi.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci mutanen kirki masu amfanuwa da sauraron Alƙur'ani, sai kuma ya bayyana halayyar wasu marasa imani masu bijire wa sauraronsa da karkata a kan sauraron wasu waƙe-waƙe da sautuka na banza waɗanda Shaiɗan yake ƙawata musu yana ingiza su ciki. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa a cikin mutane akwai wanda yake zaɓar maganganu masu shagaltarwa kamar waƙoƙin banza da kaɗe-kaɗe da labaru marasa manufa don ya ɓatar da mutane ya kautar da su daga addinin Allah ba tare da ilimi ba, ya kuma riƙa yin izgili ga ayoyin Allah. Allah ya tabbatar da cewa masu irin wannan hali suna da wata azaba mai wulaƙantarwa a ranar alƙiyama.
Da yawa daga cikin magabata na ƙwarai sun bayyana cewa ma'anar 'zance mai shagaltarwa' da aka ambata a cikin ayar yana nufin waƙe-waƙe. Daga cikin masu wannan fassara akwai Abdullahi ɗan Mas'ud da Abdullahi ɗan Abbas da Jabir ɗan Abdullahi da Sa'idu ɗan Jubair da Mujahid da Ikrima da sauransu. [Dubi, *Mausu'atut Tafsiril Ma'asur*, Juzu'i na 17, shafi na 493-500].

Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya kasance yana yin rantsuwa da Allah wanda babu abin bauta da gaskiya sai shi cewa, 'zance mai shagaltarwa' ana nufin waƙe-waƙe, har sau uku. [Dubi, Ibni Jarir, *Jami'ul Bayan*, Juzu'i na 18, shafi na 534 da Al-Baihaƙi, *As-Sunanul Kubra*, Juzu'i na 10, shafi na 225].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana mummunan halin mai shagalta da wasu maganganu ya yi watsi da Alƙur'ani da cewa, idan ana karanta masa ayoyin Allah sai kawai ya juya baya yana mai girman kai kamar ma bai ji abin da ake karanta masa ba, ya yi kunnen uwar shegu kamar wanda ya kurumce, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi masa albishir da azaba mai raɗaɗi da take jiran sa a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani shi kaɗai ba zai ishi bawa ba har sai ya gama da ayyuka nagari.

2. Tabbatar da samuwar gidan Aljanna a ranar alƙiyama. Kuma gida ne wanda yake cike da ni'imomi daban-daban da Allah ya tanadar wa bayinsa nagari.

3. Babu wani rashin lafiya a cikin Aljanna ko tsufa ko damuwa ko ɓacin rai, saboda duk waɗannan abubuwa ne da suka saba wa ni'ima da jin daɗi da Allah ya ambaci cewa su ne tagomashin Aljanna.

4. Alƙawarin Allah gaskiya ne kuma ba makawa sai ya tabbata.

Suratu Luƙman (8-9)

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ جَنَّٰتُ ٱلنَّعِيمِ ٨ خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٗاۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٩

8. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari suna da (sakamakon) gidajen Aljanna na ni'ima.

9. Suna madawwama a cikinsu; alƙawarin Allah kuwa gaskiya ne. Kuma Shi Mabuwayi ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kyakkyawar makoma ta waɗanda suka karɓi ayoyin Allah suka yi aiki da su a nan duniya, da cewa lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi kyawawan ayyuka, to suna da sakamakon gidajen Aljanna na zama waɗanda Allah ya tanadar musu don su shige su su ji daɗi a cikinsu har abada babu ranar da za a fitar da su daga cikinsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa wannan alƙawari ne tabbatacce da ya ɗauka. Kuma shi Allah mabuwayi ne babu mai cin galaba a kansa, mai hikima ne cikin halittarsa da ƙaddararsa da shari'arsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin Kaɗaitakar Allah da yin halitta da ƙalubalantar masu bautar wasu ba Allah ba da su nuna tasu halittar.

2. Kafa dalili da Tauhidin Rububiyya a kan Tauhidin Uluhiyya.

3. Duk waɗanda suke musunta Tauhidin Uluhiyya, watau kaɗaita Allah da bauta, ɓatattu ne kuma azzalumai.

Suratu Luƙman (10-11)

خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ بِغَيۡرِ عَمَدٖ تَرَوۡنَهَاۖ وَأَلۡقَىٰ فِي ٱلۡأَرۡضِ رَوَٰسِيَ أَن تَمِيدَ بِكُمۡ وَبَثَّ فِيهَا مِن كُلِّ دَآبَّةٖۚ وَأَنزَلۡنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوۡجٖ كَرِيمٍ ١٠ هَٰذَا خَلۡقُ ٱللَّهِ فَأَرُونِي مَاذَا خَلَقَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦۚ بَلِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ١١

10. Ya halicci sammai ba tare da wani ginshiƙi da kuke ganin sa ba, Ya kuma kafa manya-manyan duwatsu a cikin ƙasa don kada ta riƙa tangal-tangal da ku, Ya kuma yaɗa kowace irin dabba a cikinta. Kuma Mun saukar da ruwa daga sama sai Muka tsirar da kowane irin dangin tsiro mai ƙayatarwa.

11. Wannan (ita ce) halittar Allah, sai ku nuna min abin da waɗanda ba Shi ba suka halitta. A'a, su dai azzalumai suna cikin ɓata ne mabayyani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikar Kudurarsa da kamalar ikonsa waɗanda da su ya cancanci bauta shi kaɗai, da cewa shi ne ya halicci sammai da muke ganin su babu wasu ginshiƙai da suka tallabe su, ya kuma dasa kafaffun duwarwatsu a cikin ƙasa domin kada ta riƙa tangal-tangal da masu rayuwa a bayanta, ya kuma barbaza dangogin dabbobi iri-iri a bayan ƙasa. Sannan ya saukar da ruwan sama wanda a sanadiyyarsa ne ƙasa take tsirar da kowane nau'i na tsirrai masu ban sha'awa da amfani ga mutane da dabbobi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci kafirai masu bautar waninsa cewa ga dai waɗannan manya-manyan halittu da aka ambata duk aikinsa ne halittarsa ne shi kaɗai, su kuma sai su nuna masa abin da allolinsu da suke bauta wa suka halitta. Allah ya tabbatar musu da cewa su dai kawai azzalumai ne

da suke cikin ɓata bayyananne yayin da suka zaɓi su riƙa haɗa shi da wasu wajen bauta, alhalin sun san shi kaɗai ne ya yi halitta, gumakansu ba su halicci komai ba tunda su ma sassaƙa su aka yi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan hore wa bayinsa waɗanda ya zaɓa ilimi da hikimar gane abubuwa yadda suke.

2. Hikima ta ƙunshi sanin addini da kaifin hankali da basira da fahimtar yadda al'amura suke tare da sanya komai a mahallin da ya dace.

3. Wajabcin yi wa Allah godiya game da ni'imominsa.

4. Bayani a kan cikar wadatar Ubangiji daga amfanuwa da ɗa'ar bayinsa ko cutuwa da saɓonsu.

5. Duk wanda ya yi aiki nagari ya yi ne don amfanin kansa, duk kuma wanda ya yi mummunan aiki kansa kaɗai ya cuta.

Suratu Luƙman (12)

وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا لُقْمَٰنَ ٱلْحِكْمَةَ أَنِ ٱشْكُرْ لِلَّهِ ۚ وَمَن يَشْكُرْ فَإِنَّمَا يَشْكُرُ لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِىٌّ حَمِيدٌ ﴿١٢﴾

12. Haƙiƙa kuma Mun bai wa Luƙumanu hikima cewa: "Ka yi godiya ga Allah. Kuma duk wanda yake godewa to yana godewa ne don kansa, wanda kuwa ya kafirta to lalle Allah Mawadaci ne, Sha-yabo."

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin wani bawansa ne mutumin kirki da ya hore wa ilimi da hikima, mai suna Luƙumanu. Ya ba shi fahimtar addini da gane al'amura yadda suke.
Babu wani nassi da ya tabbata game da cewa Luƙumanu annabi ne. Yawancin malamai sun amince da cewa shi wani salihin bawa ne da Allah ya yi masa baiwar hikima da ilimi. Malaman tafsiri da na tarihi sun ambaci cewa ya rayu ne a zamanin Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a cikin garuruwan Banu Isra'ila.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci hikimomin da ya ba shi cewa, ya hore shi a kan ya yi wa Allah godiya bisa wannan ni'ima da ya yi masa, ya kuma tabbatar masa cewa duk wanda ya gode wa Allah to shi ne mai amfana da wannan godiyar, domin Allah ba shi da buƙatar komai daga godiyarsa. Duk kuma wanda ya butulce wa ni'imar da Allah ya yi masa, to ya san da cewa kansa zai cutar ba Allah ba, domin shi Allah mawadaci ne ba ya buƙatar komai a wurin kowa kuma sha-yabo ne a kowane hali.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Luƙumanu ya fara nasiharsa ga ɗansa da kiran sa 'ya kai ƙaramin ɗana', domin ya nuna masa ƙaunarsa da soyayyarsa da tausayinsa gare shi. Wannan salo ne da zai ƙara wa ɗansa fahimtar muhimmancin maganganun da zai faɗa masa.

2. Luƙumanu ya fara wa'azinsa ga ɗansa da gargaɗi a kan ya guji yin shirka da Allah, domin duk zuciyar da ake ƙoƙarin tsarkake ta da shirya ta don ta samu mataki na kamilan mutane to dole ne da farko sai an tsarkake ta daga duk wasu miyagun aƙidu da munanan ayyuka.

3. Lukumanu ya tabbatar wa da ɗansa cewa shirka zalunci ne mai girma, domin babu abu mafi muni kamar wani ya daidaita mahalicci da wanda aka halicce shi da ƙasa, ko ya daidaita wanda bai mallaki komai ba da wanda duk al'amura suke a hannunsa, ko ya daidaita tauyayye mabuƙaci da mai cikakkiyar wadata mai kamala ta kowace fuska, ko ya daidaita wanda ba zai iya ni'imtarwa daidai da ƙwayar zarra ba da wanda duk wata ni'ima ta duniya da ta lahira tasa ce, wanda babu mai yaye cuta sai shi. Shin akwai zaluncin da ya kai girman wannan? Akwai zaluncin da ya kai na wanda Allah ne ya halicce shi don ya bauta masa amma sai ya koma ya wulaƙanta kansa yana bautar wanin Allah, ya zalunci kansa da kansa? Babu shakka wannan zalunci ne mai girma.

4. Bayanin girman haƙƙoƙin iyaye a kan 'ya'yansu.

5. Bayanin wahalhalun da uwa take sha wajen ɗaukar ciki da haihuwa da renon ɗanta, yana nuna ƙarin falala da take da shi da girman haƙƙi a kan 'ya'yanta fiye da na uba.

6. Godiya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tana gaba da godiya ga kowane ne duk girman matsayinsa.

7. Godiyar bawa ga Ubangijinsa ta ƙunshi tsayawa da bautarsa, da bayar da haƙƙoƙinsa, da guje wa amfani da ni'imominsa wajen saɓa masa.

Godiya ga iyaye kuwa ta ƙunshi ya yi musu daddaɗar magana da kyautata musu a aikace, da ɗaukar nauyinsu da guje wa ɓata musu rai ta kowace fuska.

8. Babu ɗa'a ga wani mahaluki duk girmansa wajen saɓa wa mahalicci.

9. Kafircin iyaye ko fasiƙancinsu ba ya sarayar da haƙƙinsu na yi musu biyayya da kyautata musu cikin abin da bai saɓa wa Allah ba.

10. Bayani a kan yalwar ilimin Allah da cikar Kudurarsa wanda a cikin yin hakan akwai kwaɗaitarwa a kan tsoron Allah da halarto shi a zuciya a koyaushe.

11. Farawa da koyar da Tauhidi da gargaɗi a kan shirka shi ne asalin da'awar annabawa da mabiyansu, domin ana gina duk sauran ibadu ne a kan Tauhidi, don haka ake buƙatar tsayar da ginshiƙinsa kafin kowane irin gini.

12. Haramcin nuna wa mutane girman kai ko ji-ji-da-kai.

13. Haramcin tafiya cikin taƙama da ƙasaita, domin yin haka ba ɗabi'a ce ta mai tawali'u ba.

14. Umarni da guje wa ɗaga murya yayin tattaunawa ba tare da buƙatar yin hakan ba.

15. Waɗannan wasiyyoyi da Lukumanu ya yi wa ɗansa sun ƙunshi manya-manyan hikimomi, sun kuma yi ishara zuwa ga waɗanda ba a ambace su ba. Sannan kowace wasiyya ta zo tare da ambaton abin da zai kwaɗaitar a kan aiki da ita, idan umarni ce ko hani ko abin da zai sa a guje mata.

16. Waɗannan wasiyyoyi sun nuna cewa tarbiyya a Musulunci ta ƙunshi gyara halayyar mutum a zamansa na shi kaɗai da kuma gyara masa halayyarsa a wajen hulɗarsa da jama'a.

Suratu Lukman (13-19)

وَإِذْ قَالَ لُقْمَٰنُ لِٱبْنِهِۦ وَهُوَ يَعِظُهُۥ يَٰبُنَيَّ لَا تُشْرِكْ بِٱللَّهِۖ إِنَّ ٱلشِّرْكَ لَظُلْمٌ عَظِيمٌ ﴿١٣﴾ وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ حَمَلَتْهُ أُمُّهُۥ وَهْنًا عَلَىٰ وَهْنٍ
وَفِصَٰلُهُۥ فِى عَامَيْنِ أَنِ ٱشْكُرْ لِى وَلِوَٰلِدَيْكَ إِلَىَّ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٤﴾ وَإِن جَٰهَدَاكَ عَلَىٰٓ أَن تُشْرِكَ بِى مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ فَلَا تُطِعْهُمَاۖ وَصَاحِبْهُمَا فِى
ٱلدُّنْيَا مَعْرُوفًاۖ وَٱتَّبِعْ سَبِيلَ مَنْ أَنَابَ إِلَىَّۚ ثُمَّ إِلَىَّ مَرْجِعُكُمْ فَأُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٥﴾ يَٰبُنَيَّ إِنَّهَآ إِن تَكُ مِثْقَالَ حَبَّةٍ مِّنْ خَرْدَلٍ
فَتَكُن فِى صَخْرَةٍ أَوْ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ أَوْ فِى ٱلْأَرْضِ يَأْتِ بِهَا ٱللَّهُۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَطِيفٌ خَبِيرٌ ﴿١٦﴾ يَٰبُنَيَّ أَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ وَأْمُرْ بِٱلْمَعْرُوفِ وَٱنْهَ عَنِ ٱلْمُنكَرِ
وَٱصْبِرْ عَلَىٰ مَآ أَصَابَكَۖ إِنَّ ذَٰلِكَ مِنْ عَزْمِ ٱلْأُمُورِ ﴿١٧﴾ وَلَا تُصَعِّرْ خَدَّكَ لِلنَّاسِ وَلَا تَمْشِ فِى ٱلْأَرْضِ مَرَحًاۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ ﴿١٨﴾
وَٱقْصِدْ فِى مَشْيِكَ وَٱغْضُضْ مِن صَوْتِكَۚ إِنَّ أَنكَرَ ٱلْأَصْوَٰتِ لَصَوْتُ ٱلْحَمِيرِ ﴿١٩﴾

13. Kuma (ka tuna) lokacin da Lukumanu ya ce da ɗansa a yayin da yake yi masa wa'azi: "Ya kai ɗanɗana, kada ka yi shirka da Allah; lalle ita shirka zalunci ne mai girma.

14. Kuma Mun yi wa mutum wasiyya game da iyayensa, mahaifiyarsa ta ɗauke shi a cikinta rauni a kan rauni, yaye shi kuwa a cikin shekara biyu ne, saboda haka ka gode min da kuma iyayenka, makoma gare Ni take.

15. Idan kuma suka matsa maka kan ka yi tarayya da Ni game da abin da ba ka da wani sani a kansa, to kada ka bi su; kuma ka yi zaman duniya da su ta kyakkyawar hanya; ka kuma bi hanyar wanda ya mayar da al'amarinsa gare Ni. Sannan kuma zuwa gare Ni ne kawai makomarku, sai in ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa.

16. (Lukumanu ya ci gaba da cewa): "Ya kai ɗanɗana, lalle ita (kyakkyawa ko mummuna) in ta kasance daidai da ƙwayar komayya, sannan kuma ta zamanto cikin ƙaton dutse ko kuma cikin sammai ko cikin ƙasa, to Allah zai zo da ita. Lalle Allah Mai tausasawa ne, Masanin (komai).

17. "Ya kai ɗanɗana, ka tsayar da salla kuma ka yi umarni da aikata alheri, ka kuma hana aikata mummunan aiki, kuma ka yi haƙuri bisa duk abin da ya same ka; lalle wannan yana daga manyan al'amura.

18. "Kada kuma ka riƙa ɗauke wa mutane fuskarka, kuma kada ka yi tafiya a ban ƙasa kana mai taƙama. Lalle Allah ba Ya son duk wani mai taƙama, mai fariya.

19. "Kuma ka tsakaita tafiyarka, kuma ka yi ƙasa-ƙasa da muryarka. Lalle mafi munin muryoyi ita ce muryar jakai."

A cikin waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wani ɓangare na ilimi da hikima da ya ba wa Lukumanu yayin da ya zaunar da ɗansa ya yi masa wasu wasiyyoyi guda goma masu matuƙar amfani a rayuwarsa ta duniya da ta lahira.
Wasiyya ta farko, ya fara da gargaɗin sa game da haɗa Allah da wani wajen bauta, da cewa yin shirka da Allah zalunci ne mai girman gaske, domin ya ƙunshi ɗaukar haƙƙin Allah mahalicci a ba wa wani mahaluki.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Lokacin da faɗar Allah ta sauka mai cewa: 'Waɗanda suka yi imani kuma ba su gauraya imaninsu da zalunci ba, waɗannan su suke da aminci kuma su ne shiryayyu.' [*Al-An'am*, aya ta 82] sai wannan ya sa sahabban Manzon Allah (ﷺ) suka damu suka ce: "Wane ne a cikinmu bai zalunci kansa ba?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Abin ba kamar yadda

kuke zato ba ne; al'amarin ai kamar yadda Luƙumanu ne yake faɗa wa ɗansa cewa: 'Ya kai ɗana, kada ka yi shirka da Allah, lalle shirka zalunci ne mai girma.'" [Bukhari #6933 da Muslim #124].
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasiyyar farko ta Luƙumanu ga ɗansa sai ya biyo bayanta da bayanin haƙƙin iyaye, domin wannan salo ne na Alƙur'ani ambaton haƙƙin iyaye bayan batun haƙƙin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a wurare da dama.
A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya yi wa ɗan'adam wasiyya da ya kyautata wa iyayensa ya yi musu biyayya a duk abin da bai saɓa wa Allah ba. Ya tunatar da shi wahalhalun da mahaifiyarsa ta sha tun daga lokacin da ta sami cikinsa take shiga wahala, wahalar kuma tana ta ƙaruwa; wahala bayan wahala har lokacin haihuwarsa ya zo ta haife shi cikin wahala. Sannan kuma ta shiga cikin wahalar shayar da shi da kula da shi har lokacin yayensa ya yi ta yaye shi cikin shekara biyu. To sai Allah ya umarci mutum da ya gode masa a kan ni'imar da ya yi masa mai tarin yawa sannan kuma ya gode wa iyayensa a kan wahalhalun da suka sha wajen renonsa da tarbiyyarsa har ya zama cikakken mutum mai dogaro da kansa. Ya tunatar da shi cewa zuwa gare shi ne makomarsu gaba ɗaya take, a can ne Allah zai saka wa kowa gwargwadon aikinsa mai kyau ko mummuna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan'adam kashedi game da yi wa iyayensa biyayya a kan abin da ya saɓa wa shari'a, da cewa kada ya kuskura ya yi wa iyayensa biyayya lokacin da za su yi ta ƙoƙarin tilasa shi da ya yi wa Allah shirka ya bi addininsu wanda ba Musulunci ba saboda kasancewarsu su ba Musulmi ne ba, domin babu biyayya ga wani mahaluƙi wajen saɓa wa mahalicci. To amma kuma duk da haka kada ya bijire wa yi musu biyayya a cikin sauran al'amura na duniya waɗanda ba su saɓa wa addininsa ba; ya ci gaba da kyautata musu da yi musu kyakkyawar mu'amala. Allah ya nuna masa cewa ya bi tafarkin wanda ya mayar da al'amarinsa gare shi ta hanyar kaɗaita shi da bauta da yin ɗa'a gare shi, sannan ya tabbatar masa da cewa makomarsu gaba ɗaya zuwa gare shi take a ranar alƙiyama sannan zai ba su labarin duk abin da suka aikata a nan duniya, ya kuma yi musu sakayya a kai.

An karɓo daga Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wasu ayoyi na Alƙur'ani sun sauka game da ni." Ya ce: "Mahaifiyar Sa'ad ta rantse ba za ta yi masa magana ba har abada har sai ya kafirce wa addininsa, kuma ba za ta ci ko ta sha komai ba har sai ya bi ta a kan haka. Ta ce masa: 'Ka riya cewa Allah ya yi maka wasiyya a kan ka bi mahaifanka, ni kuma mahaifiyarka ce kuma ni ce nake ba ka wannan umarnin.' Ya ce: "Ta zauna a cikin wannan yanayi tsawon kwana uku, saboda wahala har ta riƙa suma. Sai wani ɗanta mai suna Umara ya je ya ba ta ruwa ta sha, sai ta shiga yi wa ɗanta Sa'ad mummunar addu'a, sai Allah ya saukar da waɗannan ayoyin." [Muslim #1748].
Wasiyya ta biyu, Luƙumanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sake jan hankalin ɗansa, ya sanar da shi cewa, mummunan aiki ko kyakkyawa komai ƙanƙantarsu, ko da kuwa kamar ƙwayar komayya ce a cikin wani babban dutse ko a can wani wuri cikin sammai ko a cikin ƙasa da babu wanda ya san da shi, to ranar alƙiyama Allah zai zo da shi domin ya yi sakayya ga bawa a kansa, lalle Allah mai zuzzurfan sani ne na komai, cikakken masani ne na yadda haƙiƙanin abubuwa suke da inda suke.
Wannan wasiyya tana nufin jan hankalin ɗansa a kan ya riƙa tuna cewa Allah yana ganin duk wani motsinsa, don haka ya riƙa kawo shi a ransa a kowane lokaci domin ya kyautata aikinsa iya ƙoƙarinsa.
Wasiyya ta uku, Luƙumanu ya sake jawo hankalin ɗansa ya umarce shi da ya tsayar da salla yadda ya kamata, watau ya kula da hukunce-hukuncenta na wajibai da mustahabbai, domin salla ita ce mafi girman ibada da gaɓoɓi suke yi.
Wasiyya ta huɗu, ya umarce shi da ya yi umarni da kyakkyawan aiki, wannan kuwa yana buƙatar shi kansa ya san abin da zai yi umarni da shi, ya kuma yi ƙoƙarin aikata shi kafin ya umarci wani da haka.
Wasiyya ta biyar, ya umarce shi da ya yi hani ga mummunan aiki, wanda shi ma yana buƙatar ya san mene ne mummuna domin ya guje shi shi kansa.
Wasiyya ta shida, ya umarce shi da ya yi haƙuri a kan duk abin da zai same shi lokacin da yake umarni da kyakkyawa ko ya hana mummuna, domin wanda duk ya ɗauki wannan aiki to lalle zai gamu da ƙalubale iri-

iri; dole sai ya yi haƙuri sannan ne zai ga amfanin abin da yake yi. Haƙuri a nan ya ƙunshi ya yi haƙuri wajen ɗa'a ga Allah da guje wa saɓon Allah, ya kuma yi haƙuri a kan ƙaddarar Allah marar kyau idan ta same shi.
Wasiyya ta bakwai, Luƙumanu ya gargaɗi ɗansa a kan ya guji ɗauke wa mutane fuska domin nuna musu girman kai, watau ya zama mai sakin fuska da haba-haba da jama'a, domin ya samu shiga zukatansu, wa'azinsa a gare su ya yi musu tasiri.An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce da ni: "Kada ka raina aikin alheri ko yaya yake, ko da kuwa ka haɗu da ɗan'uwanka ne da sakakkiyar fuska." [Muslim #2626].
Wasiyya ta takwas, ya ja kunnensa a kan yin tafiya a bayan ƙasa cikin taƙama da ji-ji-da-kai, ya nuna masa cewa lalle Allah ba ya son mai tafiya yana taƙama da ji-ji-da-kai, yana mai alfahari da ni'imar da Allah ya yi masa, yana yi wa mutane girman kai kuma ba ya gode wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: 'Wani mutum yana cikin tafiya ya caɓa ado, yana ji-ji da kansa ya taje sumarsa, sai kawai Allah ya nufi ƙasa ta haɗiye shi, yana nan yana ta gangarawa a cikinta har tashin alƙiyama.'" [Bukhari #5789 da Muslim #2088].
Wasiyya ta tara, Luƙumanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya umarci ɗansa da ya tsakaita tafiyarsa, kada ya riƙa yin ta da sauri sosai, kada kuma ya riƙa tafiya laƙaƙai-laƙaƙai, ya dai yi tafiya cikin nutsuwa baina-baina.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: 'Mutum uku Allah ba ya son su: Mutum mai fariya mai taƙama, domin kuna karantawa a cikin littafin Allah yana cewa: 'Lalle Allah ba ya son duk wani mai taƙama mai fariya; da marowaci mai yawan gori; da ɗan kasuwa mai yawan rantsuwa....'" [Ahmad #21530].
Wasiyya ta goma, Luƙumanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya umarci ɗansa da ya yi ƙasa-ƙasa da muryarsa, kada ya riƙa ɗaga muryarsa ta yadda zai cutar da wani, ya ba shi misali da cewa lalle mafi munin sauti shi ne sautin jaki domin sautinsa ya fi na kowace dabba ƙara mai muni.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: 'Idan kun ji carar zakara to ku roƙi Allah daga falalarsa domin ya ga mala'iku ne, idan kuma kuka ji kukan jaki to ku nemi tsarin Allah daga Shaiɗan domin ya ga Shaiɗan ne." [Bukhari #3303 da Muslim #2729].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ni'imomin Allah ga bayinsa dalili ne na cancantar a gode masa a yi imani da shi, ba dalili ne na a kafirce masa ba.

2. Halaccin amfanuwa da abin da yake cikin farfajiyar halittar sama da ƙasa, domin Allah ya halicce su ne ya hore su ga bayinsa domin amfaninsu, don haka za su amfana daga duk abin da bai haramta musu amfani da shi ba.

3. Sukan jayayya da musu ba a kan ilimi ba.

4. Jayayya ta ilimi da hujja da dalili don bayanin gaskiya ko rushe ƙarya ba laifi ba ne.

5. Sukan makauniyar biyayya, musamman cikin al'amuran aƙida. Kuma duk wanda ya watsar da dalili da hujja domin makauniyar biyayya ga iyaye ko shugabanni, to ya amsa kiran Shaiɗan ne.

6. Duk wanda zai ja mutane zuwa ga abin da zai jawo musu uƙubar Allah to wannan shaiɗan ne.

Suratu Luƙman (20-21)

أَلَمْ تَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَأَسْبَغَ عَلَيْكُمْ نِعَمَهُۥ ظَٰهِرَةً وَبَاطِنَةً ۗ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُجَٰدِلُ فِى ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَلَا هُدًى وَلَا كِتَٰبٍ مُّنِيرٍ ﴿٢٠﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱتَّبِعُوا۟ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُوا۟ بَلْ نَتَّبِعُ مَا وَجَدْنَا عَلَيْهِ ءَابَآءَنَآ ۚ أَوَلَوْ كَانَ ٱلشَّيْطَٰنُ يَدْعُوهُمْ إِلَىٰ عَذَابِ ٱلسَّعِيرِ ﴿٢١﴾

20. Yanzu ba kwa gani cewa Allah Ya hore muku abin da yake cikin sammai da kuma abin da yake cikin ƙasa, Ya kuma cika muku ni'imominsa na sarari da na ɓoye? Daga mutane kuma akwai waɗanda suke jayayya game da Allah ba tare da wani ilimi ko wata shiriya ba, ba kuma tare da wani littafi mai haskakawa ba.

21. Idan kuma aka ce da su: "Ku bi abin da Allah Ya saukar", sai su ce: "A'a, mu muna bin abin da muka sami iyayenmu ne a kansa." Yanzu (sa yi haka) ko da Shaiɗan ya zamanto yana kiran su zuwa ga azaba ta (wuta) mai ruruwa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake janyo hankalin kafirai zuwa ga duba cikin ayoyin Allah na sama da na ƙasa, masu nuna Kaɗaitarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da yi masa shirka ba.
Allah ya ja hankalin mutane cewa yanzu ba za su duba su ga yadda ya hore musu amfani da duk wani abu da ke cikin sammai na rana da wata da taurari; da abin da yake bayan ƙasa na dabbobi da bishiyoyi da tsirrai da shuke-shuke da ƙoramu da ma'adanai. Ya kuma ba su ni'imominsa cikakku na sarari da suke gani da idanunsu, kamar kyawawan sura ta halitta da ya yi musu, da ni'imominsa na ɓoye kamar hankali da ilimi da ya ba su? To amma abin takaici duk da ganin waɗannan ni'imomi na Allah, sai a sami wani daga cikin mutane yana jayayya da musunta Kaɗaitakar Allah ba tare da wani ilimi na wahayi daga Allah ba, ba kuma tare da wata shiriya ta hankali ko wani saukakken littafi daga Allah ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda masu irin wannan mummunar aƙida suka yi nisa domin kuwa ba hujja suke son ji ba; duk sanda aka ce musu su taho su bi wahayin da Allah ya yi wa Manzonsa (ﷺ), sai su buɗe baki suna mamaki, su ce ba za su bi ba, su kawai za su bi abin da suka tashi suka sami iyayensu da kakanninsu a kai na bautar gumaka. Sai Allah ya tambaye su cewa, shin za su bi iyayen nasu ne ko da kuwa shaiɗan ya kasance yana kiran su ne zuwa faɗawa cikin azabar wutar Jahannama ranar alƙiyama ta hanyar ɓatar da su da ya riƙa yi da bautar gumaka? Kuma su iyayen nasu suka amsa masa gayyatarsa suka zama mabiyansa masu rayuwa cikin ɗimuwa. To yanzu waɗannan ne za su fifita bin su a kan su bi wahayin da aka yi wa Manzo (ﷺ)?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin miƙa wuya ga Allah da kyautata aiki domin neman yardarsa.

2. Ikhlasi, watau yin ƙomai don Allah shi kaɗai da kuma ƙoyi da Manzon Allah, su ne rukunan samun tsira a ranar alƙiyama.

3. Duk ƙarshen al'amura yana hannun Allah ne, shi ne wanda mulkin sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu duk suke hannunsa. Sau tari mutum zai gama nasa hasashe da ƙaddarawa amma sai Allah ya kawo masa saɓanin yadda yake hasashe da ƙaddarawa domin ƙarshen dukkan al'amura na Allah ne.
4. Tsananin tausayin Manzon Allah (ﷺ) da rahamarsa ga al'ummarsa, don haka hankalinsa yake tashi yayin da ya ga wani cikin al'ummarsa a kan kafirci ko saɓo domin ya san makomarsa, idan bai tuba ba, wutar Jahannama ce.

5. Kawo Allah a zuciya koyaushe da jin tsoronsa, domin shi ne masanin abin da yake cikin zukata.

6. Karancin jin daɗin duniya da ƙanƙantarsa, don haka akan iya jiyar da kafiri daɗin duniya fiye da wani Musulmi.

7. Azabar kafirai a lahira mai tsanani ce.

Suratu Luƙman (22-24)

*وَمَن يُسۡلِمۡ وَجۡهَهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ فَقَدِ ٱسۡتَمۡسَكَ بِٱلۡعُرۡوَةِ ٱلۡوُثۡقَىٰۗ وَإِلَى ٱللَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلۡأُمُورِ ٢٢ وَمَن كَفَرَ فَلَا يَحۡزُنكَ كُفۡرُهُۥٓۚ إِلَيۡنَا مَرۡجِعُهُمۡ فَنُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٢٣ نُمَتِّعُهُمۡ قَلِيلٗا ثُمَّ نَضۡطَرُّهُمۡ إِلَىٰ عَذَابٖ غَلِيظٖ ٢٤

22. Wanda kuma ya miƙa kansa ga Allah, yana kuma mai kyautatawa, to haƙiƙa ya yi riƙo da igiya ƙwaƙƙwara. Kuma ƙarshen al'amura zuwa ga Allah ne.

23. Duk kuwa wanda ya kafirta, to kada kafircinsa ya ɓata maka rai. Zuwa gare Mu ne kawai makomarsu take, sai Mu ba su labarin abin da suka aikata. Lalle Allah Masanin abin da yake cikin ƙiraza ne.

24. Za Mu jiyar da su daɗi ɗan kaɗan sannan Mu tilasta su zuwa ga azaba mai kauri.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin mutumin da ya miƙa wuyansa ga Allah ya kaɗaita shi da bauta ya kuma kyautata aikinsa, Allah ya tabbatar masa da cewa ya yi riƙo da ƙwaƙƙwarar igiya wadda idan bawa ya riƙe ta to ya kuɓuta, domin ba zai ji tsoron ta tsinke masa ba. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ƙarshen al'amura zuwa gare shi za su koma, zai kuma yi wa kowa sakayya a kan aikinsa mai kyau da mummuna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) game da cutarwar da yake ta gamuwa da ita daga mushirikai da tsananin taurin kansu, da cewa duk wanda ya kafirta daga cikinsu to kada kafircinsa ya ɗaga wa Manzon Allah (ﷺ) hankali har ya sa shi cikin damuwa, domin ga Allah ne kawai makomarsu take ranar alƙiyama ya kuma ba su labarin duk munanan ayyukan da suka yi a duniya, ya kuma yi musu sakayya a kansu, ba abin da suka isa su ɓoye masa, domin lalle shi masanin duk abin da yake cikin zukata ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa jin daɗin da ya ba wa kafirai a nan duniya ba wani abin a zo a gani ba ne; ɗan ƙanƙani ne iya rayuwarsu ta duniya; ranar alƙiyama zai tilasta musu shiga cikin azaba matsananciya ta wutar Jahannama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayani a kan cewa mushirikan farko na wannan al'umma sun yarda da Tauhidin Rububiyya, watau kaɗaita Allah da ayyukansa, ba sa gardama a kan haka.

2. Nuni a kan cewa yarda da Tauhidin Rububiyya yana lizimta wa mutum lalle ya amince da Tauhidin Uluhiyya, watau ya kaɗaita Allah wajen ibada, rashin samun haka daga gare shi yana nuna tufka da warwara a fili.

3. Shar'anta faɗar '*Al-hamdu lillahi*' yayin da hujja ta bayyana ga abokin husuma.

Suratu Luƙman (25-26)

وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُۚ قُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٢٥﴾ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِۚ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْغَنِيُّ ٱلْحَمِيدُ ﴿٢٦﴾

25. Tabbas kuma in ka tambaye su: “Wane ne ya halicci sammai da ƙasa?” Tabbas za su ce: “Allah ne.” To ka ce: “*Alhamdu lillahi*.” A’a, yawancinsu dai ba sa sanin (haka).

26. Abin da yake cikin sammai da ƙasa na Allah ne. Lalle Allah Shi ne Mawadaci, Sha-yabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mushirikai masu bautar gumaka ba Allah ba sun yarda da cewa Allah ne ya halicci sammai da ƙasa, domin idan da Manzon Allah (ﷺ) zai tambaye su game da haka, Allah ya tabbatar masa cewa tabbas za su amsa masa da cewa Allah ne mahaliccinsu. Sai Allah ya umarci Manzonsa ya faɗa musu cewa yabo da godiya sun tabbata ga Allah wanda ya bayyana hujja a kansu, to amma yawancinsu ba su san wane ne ya cancanci yabo da godiya ba saboda tsantsar jahilcinsu. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk abin da yake cikin sammai da wanda yake a ƙasa nasa ne, domin halittarsa ne mallakarsa ne kuma bayinsa ne, kuma lalle shi mawadaci ne ba ya da buƙatar komai a wajen bayinsa, kuma shi ne sha-yabo a duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan bayar da misali domin kusanto da ma’ana zuwa ga fahimtar masu sauraro.

2. Bayani a kan cewa duk yawan ilimin da Allah zai ba wa ‘yan’adam ba komai ba ne idan an kwatanta shi da ilimin Allah.

3. Bayanin ƙarfin Kudurar Allah da kuma nuna cewa komai sauƙinsa ɗaya ne a wurin Allah, babu wani abu mai wahala ko wanda zai gagare shi (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Luƙman (27-28)

وَلَوْ أَنَّمَا فِي ٱلْأَرْضِ مِن شَجَرَةٍ أَقْلَٰمٌ وَٱلْبَحْرُ يَمُدُّهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦ سَبْعَةُ أَبْحُرٍ مَّا نَفِدَتْ كَلِمَٰتُ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٢٧﴾ مَّا خَلْقُكُمْ وَلَا بَعْثُكُمْ إِلَّا كَنَفْسٍ وَٰحِدَةٍۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ بَصِيرٌ ﴿٢٨﴾

27. Idan kuwa da a ce, duk bishiyar da take bayan ƙasa alƙaluma ne, kogi kuma (ya zama tawadarsu), bayansa kuma akwai wasu kogunan guda bakwai ƙari a kansa to kalmomin na Allah ba za su ƙare ba. Lalle Allah Mabuwayi ne, Mai hikima.

28. Halittarku da tayar da ku bai wuce tamkar na rai ɗaya ba. Lalle Allah Mai ji ne, Mai gani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yalwa da faɗin iliminsa marar iyaka. Ya buga misali don kusanto da ma’anar zuwa ga ƙwaƙwalen masu sauraro, da cewa, da a ce duk bishiyoyin da suke bayan ƙasa za a yi guntu-guntu da su, a fere su su zama alƙaluman rubutu, sannan duk wani kogi a duniya a mayar da shi tawwada ta rubutu, sannan a ƙara da wasu kogunan bakwai waɗanda su ma za su zama ƙarin tawwadar rubutu, sannan duk a haɗa su a yi ta rubuta kalmomin Allah da su, to da ba su iya ƙare kalmominsa ba, domin ba su da iyaka ko maƙura, sai dai waɗannan alƙaluma da wannan tawwada su ƙare

ƙarƙaf. Allah ya tabbatar da cewa lalle shi mabuwayi ne babu mai iya rinjayar sa, mai hikima ne cikin duk maganganunsa da ayyukansa.
Sai kuma ya bayyana musu ƙarfin Kudurarsa bayan yalwar iliminsa, da cewa halittar mutane gaba ɗayansu da sake tashinsu domin yi musu hisabi a ranar alƙiyama bai wuce gwargwadon halittar rai ɗaya ba a wajen Allah, saboda tsananin sauƙin abin a wurinsa. Lalle Allah mai ji ne mai gani ne, sauraron wani sauti ba zai hana shi sauraron wani ba, hakanan ganin wani abu ba zai hana shi ganin wani ba, don haka halittar wani rai ba zai shagaltar da shi daga halittar wani ran ba ko tashinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Raguwar dare da yini da ƙaruwarsu da hore amfanin rana da wata, duk ayoyi ne masu nuna kamalar Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ni'imominsa ne waɗanda ya cancanci godiya a kansu.

2. Bayanin cikar tsarin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake gudanar da halittun sammai da ƙasa a kansa da ganin damarsa zuwa lokacin da ya ƙayyade musu. Idan lokacin ya cika zai yi izini komai ya wargaje, domin ya tabbatar da ikonsa.

3. Haƙuri da godiya hanyoyi ne guda biyu na samun izina daga ayoyin Allah.

4. Yana daga babban butulci ga Allah a nuna masa ikhlasi a lokacin tsanani sannan a butulce masa a lokacin yalwa.

5. Allah yakan karɓi addu'ar wanda yake cikin matsuwa ko da kuwa kafiri ne.

Suratu Luƙman (29-32)
أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ كُلّٞ يَجۡرِيٓ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى وَأَنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ٢٩ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدۡعُونَ مِن دُونِهِ ٱلۡبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡكَبِيرُ ٣٠ أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱلۡفُلۡكَ تَجۡرِي فِي ٱلۡبَحۡرِ بِنِعۡمَتِ ٱللَّهِ لِيُرِيَكُم مِّنۡ ءَايَٰتِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّكُلِّ صَبَّارٖ شَكُورٖ ٣١ وَإِذَا غَشِيَهُم مَّوۡجٞ كَٱلظُّلَلِ دَعَوُاْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ فَلَمَّا نَجَّىٰهُمۡ إِلَى ٱلۡبَرِّ فَمِنۡهُم مُّقۡتَصِدٞۚ وَمَا يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا كُلُّ خَتَّارٖ كَفُورٖ ٣٢

29. Yanzu ba ka gani cewa Allah Yana shigar da dare cikin rana, Yana kuma shigar da rana cikin dare, Ya kuma hore (muku) rana da wata, kowannensu yana tafiya zuwa ga lokaci iyakantacce, kuma lalle Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne?

30. Wannan kuwa (suna samuwa ne) saboda Allah Shi ne Gaskiya, lalle kuma abin da suke bauta wa ba Shi ba ƙarya ne, lalle kuma Shi Allah Maɗaukaki ne, Mai girma.

31. Ba ka gani cewa jiragen ruwa suna tafiya a cikin kogi da ni'imar Allah, don Ya nuna muku (wasu) daga ayoyinsa? Lalle a game da wannan akwai ayoyi ga duk mai yawan haƙuri, mai yawan godiya.

32. Idan kuwa wata igiyar ruwa kamar duwatsu ta kere su, sai su roƙi Allah suna tsantsanta addini a gare Shi, to kuma idan Ya tserar da su zuwa gaci, to akan sami tsaka-tsaki daga cikinsu. Kuma babu mai yin jayayya da ayoyinmu sai duk wani mayaudari, mai butulci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana isarsa da Kaɗaitakarsa wajen sarrafa halittunsa na sama da na ƙasa. Allah ya nuna wa ɗan'adam yadda yake shigar da dare cikin yini don tsawonsa ya ragu shi kuma yini ya ƙara tsawo, wani lokaci kuma ya shigar da yini cikin dare, domin tsawonsa ya ragu shi kuma dare ya ƙaru. Haka kuma yadda ya hore tafiyar rana da wata kowannensu yana tafiya a kan hanyarsa har zuwa wani ƙayyadadden lokaci da ya tsara. Allah kuma masanin abin da bayinsa suke aikatawa ne, babu abin da yake ɓuya gare shi na ayyukansu kuma zai yi musu sakayya a kai.
Sai kuma ya bayyana cewa wannan gudanar da iko nasa da yadda yake sarrafa halittunsa shi yake tabbatar da cewa, shi ne Allah Ɗaya kuma shi ne tabbas, gaskiya a Zatinsa da siffofinsa da ayyukansa, kuma ko shakka babu abin da mushirikai suke bauta wa ba shi ba, ƙarya ne marar tushe. Don haka Allah shi ne maɗaukaki da Zatinsa da galabarsa da matsayinsa a kan dukkan halittunsa; babu wani abu sama da shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake jawo hankalin mutane don su lura da ayoyin da suke nuna kamalar ikonsa da rahamarsa ga bayinsa, ya nuna wa ɗan'adam yadda jiragen ruwa suke gudu a kan teku cikin luɗufinsa da horewarsa, domin ya nuna wa mutane manya-manyan ayoyinsa masu nuna girman Kudurarsa da rahamarsa. Sai kuma ya bayyana cewa lalle a game da waɗannan abubuwa akwai ayoyi ga duk mai yawan haƙuri a kan abin da zai same shi marar daɗi, mai yawan godiya a kan abin da zai same shi na ni'imomin Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan hali na mutane waɗanda ba sa tunawa da Allah sai sun shiga cikin wata musifa da cewa, idan suka shiga jirgin ruwa igiyar ruwa ta taso ta kewaye su kamar manya-manyan duwatsu, suka tabbatar za su hallaka, sai nan take su shiga kiran Allah tare da tsantsanta addu'a gare shi ba tare da sun tuna allolinsu ba, to amma da zarar ya amsa musu addu'o'insu ya tserar da su zuwa tudu sun kuɓuta daga hallakar nutsewa a ruwa, to sai ka samu wani daga cikinsu yana tsaka-tsaki, bai tsaya ya yi wa Allah cikakkiyar godiya da ta wajaba ya yi ba, sai kuma a samu wani daga cikinsu ya shiga jayayya da ni'imar da Allah ya yi masa, amma kuma babu mai jayayya da ayoyin Allah sai wanda yake mayaudari, wanda ya yi wa Allah alƙawarin cewa idan ya kuɓutar da shi zai gode masa, amma kuma sai ya butulce wa ni'imomin da Allah ya yi masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dangantaka ta haihuwa ko ta zumunci ba za ta amfanar da bawa ba ranar alƙiyama; abin da zai yi masa amfani shi ne imaninsa da ayyukansa na ƙwarai.

2. Shagalta da duniya da gafala ga barin yi wa lahira tanadi yana daga cikin ruɗin duniya da na Shaiɗan.

3. Allah ne kaɗai ya keɓanta da sanin mabuɗan gaibu guda biyar.

Suratu Luƙman (33-34)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُواْ رَبَّكُمۡ وَٱخۡشَوۡاْ يَوۡمٗا لَّا يَجۡزِي وَالِدٌ عَن وَلَدِهِۦ وَلَا مَوۡلُودٌ هُوَ جَازٍ عَن وَالِدِهِۦ شَيۡـٔٗاۚ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞۖ فَلَا تَغُرَّنَّكُمُ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا وَلَا يَغُرَّنَّكُم بِٱللَّهِ ٱلۡغَرُورُ ٣٣ إِنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥ عِلۡمُ ٱلسَّاعَةِ وَيُنَزِّلُ ٱلۡغَيۡثَ وَيَعۡلَمُ مَا فِي ٱلۡأَرۡحَامِۖ وَمَا تَدۡرِي نَفۡسٞ مَّاذَا تَكۡسِبُ غَدٗاۖ وَمَا تَدۡرِي نَفۡسُۢ بِأَيِّ أَرۡضٖ تَمُوتُۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرُۢ ٣٤

33. Ya ku mutane, ku kiyaye dokokin Ubangijinku, kuma ku ji tsoron ranar da mahaifi ba zai amfana wa ɗansa komai ba, kuma ɗan shi ma ba zai amfana wa mahaifinsa komai ba. Lalle alƙawarin Allah gaskiya ne; to kada rayuwar duniya ta ruɗe ku, kuma (Shaiɗan) mai ruɗarwa ya ruɗe ku game da Allah.

34. Lalle Allah a wurinsa ne (kaɗai) sanin lokacin tashin alƙiyama yake, kuma (Shi) Yake saukar da ruwa, (Shi) kuma Yake sane da abin da yake cikin mahaifu; ba kuwa wani rai da yake sane da abin da zai aikata gobe, ba kuma wani rai da yake sane da ƙasar da zai mutu. Lalle Allah Shi ne Masani, Mai cikakken ilimi.

A ayoyi biyu na ƙarshen Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo mutane ya umarce su da yin taƙawa gare shi, ta hanyar kiyaye dokokinsa da bin umarninsa da guje wa haninsa, ya kuma umarce su da su ji tsoron wata rana wadda uba ba zai amfana wa ɗansa komai ba, shi ma kuma ɗan ba zai amfana wa mahaifinsa komai ba; babu ɗaya daga cikinsu da zai ƙara wa ɗaya ladansa ko ya rage masa zunubbansa, kowa daga shi sai aikinsa. Allah ya tabbatar musu da cewa zuwan wannan rana alƙawari ne da Allah ya riga ya yi, kuma shi alƙawarinsa tabbas ne, don haka su shiga taitayinsu kada rayuwar duniya da sha'awace-sha'awacenta su ruɗe su, kada kuma su bari Shaiɗan ya yaudare su, ya nuna musu cewa ai Allah mai haƙuri ne mai gafara, alhali sun bijire wa dokokinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mabuɗan gaibinsa guda biyar waɗanda bai damƙa saninsu a hannun wani mahaluƙi ba, kamar haka:

Na farko, sanin lokacin tashin alƙiyama. Wannan ilimi Allah ne kaɗai ya bar wa kansa saninsa; bai sanar da wani mala'ika makusanci ba, ko wani annabi manzo.
Na biyu, shi ne mai saukar da ruwan sama sanda ya ga dama a inda ya ga dama, babu wanda ya san haka sai shi.
Na uku, shi kaɗai ne ya san abin da yake cikin mahaifu na duk wata halitta mace, mutum ko dabba ko ƙwaro, shi ne ya san komai da ya danganci abin da ke ƙunshe cikin mahaifa, ya san mace ce ko namiji, nagari ne ko ba nagari ba, mai wadata ne ko faƙiri ne, ɗan wuta ne ko ɗan Aljanna. Ya san komai na halittarsa tun daga lokacin shigarta mahaifa har zuwa makomarta ta ƙarshe. Babu wanda ya san wannan sai Allah shi kaɗai.
Na huɗu, babu wanda ya san me zai aikata gobe na alheri ko na sharri, na addininsa ko na duniyarsa. Allah ne kaɗai ya san haka.
Na biyar, babu wani rai da ya san a wace ƙasa zai mutu; a tudu ne ko a kwari ko a kan dutse ko cikin ruwa; Allah ne kaɗai ya keɓanta da sanin duk waɗannan al'amura. Lalle Allah masanin komai ne cikinsa da wajensa babu abin da yake ɓuya gare shi.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ce: 'Mabuɗan gaibu biyar ne babu wanda ya san su sai Allah, babu wanda ya san abin da mahaifa take ragewa (na lokaci) sai Allah; babu wanda ya san me zai faru gobe sai Allah; babu wani rai da ya san inda zai mutu sai Allah; kuma babu wanda ya san lokacin tashin alƙiyama sai Allah.'"

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: "Duk wanda ya riya cewa Annabi (ﷺ) yana ba da labarin abin da zai faru gobe, to lalle ya yi wa Allah ƙarya babba, Allah yana cewa: 'Ka ce: Waɗanda suke sammai da waɗanda suke ƙasa babu wanda ya san gaibu sai Allah.'" [Muslim #177].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nuna girman sha'anin Alƙur'ani da mu'ujizarsa.

2. Tabbatar da annabcin Manzon Allah (ﷺ) da kuma cewa Alƙur'ani wahayi ne da Allah ya yi masa.

3. Alƙur'ani shi ne mafi girman abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tarbiyyanci halittunsa da shi wanda kuma ya ƙunshi duk wani tsari da zai gyara rayuwar `yan'adam ya kyautata halayyarsu.

4. Rushe da’awar mushirikai ta cewa Annabi (ﷺ) shi ne ya ƙirƙiri Alƙur’ani ba daga Allah yake ba.

5. Hikimar saukar da Alƙur’ani ita ce gargaɗin mutane domin su bar ɓata su kama shiriya.

6. Bayanin cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko Annabinsa Muhammadu ne zuwa ga mutanen da wani manzo gabaninsa bai zo ya gargaɗe su ba, don haka da zuwansa ne hujjar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta tsayu a kansu.

32-Suratus Sajda

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Mafi shaharar sunan wannan Sura shi ne '*As-Sajda*'. Shi ne yake rubuce a cikin *masahifu* da ke hannun Musulmai a yau. Shi kuma ne sunanta da ya zo a cikin wasu littattafan hadisi.
Hakanan ana kiranta da suna '*Alif Lam Mim Tanzilu*' [Dubi, Tirmizi #2892 da Nasa'i #955].
Wani lokaci kuma ana kiran ta da sunan '*Alif Lam Mim Tanzilus Sajda*' [Dubi, Bukhari #891 da Muslim #879].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Maganar yawancin malaman tafsiri ita ce cewa, wannan Sura gaba ɗayanta *Makkiyya* ce. An ruwaito daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) cewa, ya togace ayoyi huɗu daga cikinta, watau daga aya ta 18 zuwa ta 21. Amma maganar farko ita ce ingantacciya.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta saba'in da uku (73) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratun Nahli*' kafin '*Suratu Nuh'*.

4. Adadin ayoyinta:
Yawancin malamai sun lissafa ayoyinta da cewa talatin ne (30). Amma a wurin mutanen Basra suna ganin adadinsu ishirin da tara ne (29).

5. Falalarta:
(a) Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ruwaito cewa Annabi (ﷺ) ya kasance a duk sallar asubahi ta ranar Juma'a yana karanta '*Alif Lam Mim Tanzilu*' a raka'ar farko, a raka'a ta biyu kuma sai ya karanta *Surar 'Hal Ata*' [Bukari #891 da Muslim #880].
(b) An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya kasance ba ya yin barci har sai ya karanta '*Alif Lam Mim Tanzilus Sajda*' da '*Tabarakal Lazi Bi Yadihil Mulk*' [Ahmad #14659 da Tirmizi #1320].

6. Babban Jigonta:
Tana magana ne a kan tabbatar da Kaɗaitakar Allah da gaskiyar manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ) da dalilai masu ƙarfi waɗanda hankalin ɗan'adam yake iya fahimtar su da gaggawa.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Nuni zuwa ga girman matsayin Alƙur'ani da tabbatar da cewa shi wahayi ne daga Allah da tsawatarwa ga mushirikai masu da'awar cewa Alƙur'ani ƙarya ne.

• Kafa musu ƙwaƙƙwaran dalili a kan ɓacin abin da suke bauta wa ba Allah ba; ta hanyar tabbatar musu da cewa Allah shi ne mahaliccin sammai da ƙasa shi kaɗai ba tare da abokin tarayya ba.
• Magana a kan tashi bayan mutuwa da kafa hujja a kan yadda Allah ya fari halittar ɗan'adam da zurriyarsa da kwatanta wannan da raya ƙasa bayan mutuwarta. A cikin haka kuma ya yi musu bayanin cewa raya ƙasa bayan mutuwarta ni'ima ce da bai kamata su kafirce wa wanda ya yi musu ita ba.
• Sukan waɗanda suka musanta Kaɗaitakar Allah da yi musu alƙawarin narko mai tsanani, sannan da yabon waɗanda suka ba da gaskiya da ayoyin Allah da yi musu kyakkyawan alƙawari na gidan Aljanna.
• Tabbatar da manzancin Manzo mai girma wanda Allah ya shiryar da wata babbar al'umma ta hannunsa.
• Tunatarwa game da azabar da ta auka wa al'ummun farko da suka ƙaryata manzaninsu, domin wannan ya zama wa'azi ga na bayansu, tare da nuna musu cewa muminan ne dai za su yi nasara komai daɗewa.
• Umartar Manzon Allah (ﷺ) da ya kawar da kansa daga kafurai ya jira nasarar Allah da ya yi masa alƙawarin zuwanta.

Suratus Sajda (1-3)

الٓمٓ ۝١ تَنزِيلُ ٱلۡكِتَٰبِ لَا رَيۡبَ فِيهِ مِن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ۝٢ أَمۡ يَقُولُونَ ٱفۡتَرَىٰهُۚ بَلۡ هُوَ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَ لِتُنذِرَ قَوۡمٗا مَّآ أَتَىٰهُم مِّن نَّذِيرٖ مِّن قَبۡلِكَ لَعَلَّهُمۡ يَهۡتَدُونَ ۝٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. ALIF LAM MIM.

2. Saukar da Littafin da babu kokwanto a cikinsa daga Ubangijin talikai ne.

3. Ko kuwa suna cewa (Annabi Muhammadu) ƙirƙirar sa ya yi?" Ba haka ne ba, shi dai (Alƙur'ani) gaskiya ne daga Ubangijinka yake, don ka gargaɗi mutanen da wani mai gargaɗi bai zo musu gabaninka ba, don su shiriya.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori gabaninta da haruffa makamantansu. [Duba farkon tafsirinmu na *Suratul Baƙara* don ƙarin bayani].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wannan Alƙur'ani da Manzonsa Muhammadu (ﷺ) ya zo da shi saukakke ne daga gare shi, kuma babu wani kokwanto a kansa.
Ya kuma bayyana cewa kafirai waɗanda suka ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) suna da'awar cewa wai Annabi (ﷺ) shi ne ya ƙirƙiri Alƙur'ani ya danganta shi ga Allah, wanda ba haka al'amarin yake ba. Shi Alƙur'ani gaskiya ne da babu kokwanto a kansa, saukakke ne daga Allah wanda shi ne Ubangijin Manzon Allah, kuma ya saukar masa da shi ne domin ya gargaɗi wasu mutane, watau Larabawa da babu wani manzo gabaninsa da ya zo ya gargaɗe su da azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), domin su shiriya su kama gaskiya su yi aiki da ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin tsawon lokacin da Allah ya halicci sammai da ƙasa da abin da ke a tsakaninsu a cikinsa. Wannan kuma yana nuna kamalar Kudurar Allah da cikar hikimarsa da yin abin da ya ga dama.

2. Tabbatar da siffar daidaito a kan Al'arshi ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) amma daidaiton da ya dace da shi.

3. Nuna wa mutane cewa lallai su riƙi Allah shi kaɗai ne majiɓincin al’amuransu, su kuma nemi taimakonsa shi kaɗai a cikin dukkan buƙatunsu; su sani babu mai iya cutar da su ko ya amfane su ba da saninsa ba.

4. A wannan aya ta 5 Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna gwargwadon tsawon yini a wurinsa, watau shekara dubu a lissafin mutane na duniya. A cikin *Suratul Ma’arij* aya ta 4 kuwa ya nuna cewa daidai yake da shekara dubu hamsin na lissafin duniya.
Malamai sun yi ƙoƙarin haɗa tsakanin ayoyin biyu ta fuskoki guda biyu:
Fuska ta farko, yinin shekara dubu da aka ambata a nan yana nuni ne zuwa ga gwargwadon tafiyar al’amarin da Allah ya tsara da hawansa sama zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Yinin shekara dubu hamsin kuwa da ya zo a cikin ‘*Suratul Ma’arij’* yana nufin yinin ranar alƙiyama ne. Ibn Abi Hatim ya ruwaito wannan daga abdullahi ɗan Abbas. [Dubi, *tafsirin Ibn Abi Hatim* #18987].
Fuska ta biyu, ita ce duk wuraren biyu ana nufin a ranar alƙiyama ne, kuma wannan saɓani yana da alaƙa ne da bambacin halin mumini da na kafiri a ranar alƙiyama; kafiri zai ga daɗewar yinin ya kai tsawon shekara dubu hamsin na duniya, saboda tsananin wahalar da yake ciki, yayin da shi kuwa mumini zai gan shi kamar tsawon shekara dubu ɗaya ne.
A tattare da halittar ɗan’adam akwai ni’imomi masu girma waɗanda ya wajaba a kansa ya yi wa Allah godiya saboda su, to amma ‘yan kaɗan ne cikin bayin Allah suke yi masa godiya.

Suratus Sajda (4-9)
ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ مَا لَكُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَلِىٍّ وَلَا شَفِيعٍۚ أَفَلَا تَتَذَكَّرُونَ ۝٤ يُدَبِّرُ ٱلۡأَمۡرَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ثُمَّ يَعۡرُجُ إِلَيۡهِ فِى يَوۡمٍ كَانَ مِقۡدَارُهُۥٓ أَلۡفَ سَنَةٍ مِّمَّا تَعُدُّونَ ۝٥ ذَٰلِكَ عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ۝٦ ٱلَّذِىٓ أَحۡسَنَ كُلَّ شَىۡءٍ خَلَقَهُۥۖ وَبَدَأَ خَلۡقَ ٱلۡإِنسَٰنِ مِن طِينٍ ۝٧ ثُمَّ جَعَلَ نَسۡلَهُۥ مِن سُلَٰلَةٍ مِّن مَّآءٍ مَّهِينٍ ۝٨ ثُمَّ سَوَّىٰهُ وَنَفَخَ فِيهِ مِن رُّوحِهِۦۖ وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَٱلۡأَفۡـِٔدَةَۚ قَلِيلًا مَّا تَشۡكُرُونَ ۝٩

4. Allah ne Wanda Ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu cikin kwana shida sannan Ya daidaita bisa Al’arshi; ba ku da wani majiɓincin al’amari ko mai ceto bayansa. Yanzu me ya sa ba kwa wa’azantuwa?

5. Yana shirya al’amari daga sama zuwa ƙasa sannan (al’amarin) ya hau zuwa gare Shi a cikin wani yini da gwargwadon (tsawonsa) yake shekara dubu ne daga abin da kuke ƙirgawa.

6. Wannan (Shi ne) Masanin ɓoye da sarari, Mabuwayi, Mai rahama.

7. Wanda Ya kyautata kowane abu da ya halicce shi; kuma Ya fari halittar mutum daga taɓo.

8. Sannan Ya sanya zuriyarsa daga tataccen ruwa wulaƙantacce.

9. Sannan Ya daidaita shi, Ya kuma busa masa daga ruhinsa; kuma Ya sanya muku ji da gani da zukata. Kaɗan ne ƙwarai kuke godewa.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da ingancin manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ), sai kuma ya bayyana dalilai masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da cancantar a bauta masa shi kaɗai, da cewa shi ne wanda ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu cikin kwana shida, waɗanda suka fara daga Lahadi zuwa Juma’a, duk kuwa da kasancewar shi mai iko ne ya halicce su cikin lokacin da ke ƙasa da ƙiftawar ido. Sannan ya daidaita a kan Al’arshi daidaito wanda ya dace da shi.

Ya tabbatar wa da mutane cewa ba su da wani wanda zai jiɓinci al’amuransu in ba shi ba, ko kuma wanda zai iya ceton su a wajen Ubangijinsu, ya kuɓutar da su daga azabarsa idan ya yi niyyar azabtar da su. Sai kuma ya ja hankalinsu da cewa me ya sa ba za su yi tunani ba su fahimci cewa wanda ya halicci sammai da ƙasa da abin da ke tsakaninsu ya kuma daidaita a kan Al’arshinsa shi ne kaɗai ya cancanci su bauta wa ba wani ba?

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa shi ne yake tsara al’amuran dukkan halittu na cikin sammai da ƙasa, sannan wannan al’amarin ya hau zuwa gare shi a cikin wani yini da gwargwadon tsawonsa yake shekara dubu ne daga irin lissafin mutane na duniya.

Ya tabbatar musu cewa mai tsara waɗannan al’amura duka shi ne wanda ya san abin da yake ɓoye da na sarari, shi ne kuma Mabuwayi da babu mai iya ja da shi wanda yake azabtar da maƙiyansa, shi ne kuma mai rahama wanda yake jin ƙan bayinsa muminai. Shi ne kuma wanda ya kyautata duk wani abu da ya halitta, ya yi masa halittar da ta dace da shi, ta kuma dace da hikimar halittarsa. Sai kuma ya bayyana cewa ya fara halittar mutum na farko daga taɓo ba tare da ya kwaikwaya a wurin wani ba. mutum na farko shi ne Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya sanya halittar zurriyar Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a bayansa daga ruwa wulaƙantacce, watau maniyyi wanda yake fita daga jikin shi ɗan’adam, sannan ya cika halittarsa ya yi shi daidaitaccen mutum, ya busa masa ruhinsa, ta hanyar aiko masa mala’ika wanda ya wakilta masa busa rayuka, tun daga lokacin da ɗan’adam ya zama mutum mai rai a jikinsa.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutane wasu ni’imomin da ya yi musu a halittarsu yayin da ya sanya musu ji da gani ya kuma ba su zukata waɗanda za su yi tunani da su. Duk waɗannan ni’imomi manya-manya da ya yi wa mutane domin su gode masa ne ta hanyar bauta masa shi kaɗai ba tare da sun yi masa shirka ba, to amma sai ya zamanto kaɗan ne ƙwarai suke gode masa a kan waɗannan ni’imomi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da aƙidar tashi bayan mutuwa.

2. Kafirce wa haɗuwa da Allah shi ne babban zunubin da yake haifar da duk wani saɓo.3. Bayanin cewa Allah ya wakilta mala’ika domin karɓar rayuka. Sai dai kuma yana da mataimaka cikin mala’iku da suke taya shi wannan aiki.

Suratus Sajda (10-11)

وَقَالُوٓاْ أَءِذَا ضَلَلۡنَا فِي ٱلۡأَرۡضِ أَءِنَّا لَفِي خَلۡقٖ جَدِيدِۭۚ بَلۡ هُم بِلِقَآئِ رَبِّهِمۡ كَٰفِرُونَ ١٠ ۞قُلۡ يَتَوَفَّىٰكُم مَّلَكُ ٱلۡمَوۡتِ ٱلَّذِي وُكِّلَ بِكُمۡ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ تُرۡجَعُونَ ١١

10. Suka kuma ce: “Yanzu idan muka zagwanye a cikin ƙasa, ashe za a sake sabunta halittarmu?” A’a, su dai suna kafircewa ne da saduwa da Ubangijinsu.

11. Ka ce (da su): “Mala’ikan mutuwa ne wanda aka wakilta muku zai karɓi ranku sannan kuma ga Ubangijinku za a komar da ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kafirci da wautar mushirikai masu ƙaryata tashi bayan mutuwa, domin su a ganinsu ta yaya bayan sun mutu an binne su a cikin ƙasa sun ɓace a cikinta, sun zama turɓaya sannan kuma a ce za a sake tayar da su a yi musu sabuwar halitta? Suna ganin wannan wata magana ce da hankalinsu ba zai iya ɗaukan ta ba. Sai Allah ya nuna musu cewa suna faɗar wannan

batu ne kawai domin da ma can sun kafirce wa haɗuwa da Ubangijinsu, ba su yi imani da tashi bayan mutuwa ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya mayar musu da martani cewa mala'ikan mutuwa wanda aka wakilta shi ya karɓi rayukansu shi ne zai karɓi rayukansu idan ajalinsu ya yi, sannan zuwa ga Allah ne kaɗai za a mayar da su ranar alƙiyama domin ya yi musu hisabi ya saka wa kowa a kan aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rashin amfanin imanin kafiri yayin da ya ga azabar Allah.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya yanke hukuncin cewa sai ya cika Jahannama da kafirai na mutane da aljannu.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai gina sakamako ne ranar alƙiyama a kan ayyukan bayi; wanda ya aikata alheri ya ga alheri, wanda kuwa ya aikata sharri shi ma ya ga sharri.

4. Azabar kafirai a Jahannama madawwamiya ce ba mai yankewa ba.

Suratus Sajda (12-14)
وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلْمُجْرِمُونَ نَاكِسُوا۟ رُءُوسِهِمْ عِندَ رَبِّهِمْ رَبَّنَآ أَبْصَرْنَا وَسَمِعْنَا فَٱرْجِعْنَا نَعْمَلْ صَٰلِحًا إِنَّا مُوقِنُونَ ﴿١٢﴾ وَلَوْ شِئْنَا لَءَاتَيْنَا كُلَّ نَفْسٍ هُدَىٰهَا وَلَٰكِنْ حَقَّ ٱلْقَوْلُ مِنِّى لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنَ ٱلْجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ أَجْمَعِينَ ﴿١٣﴾ فَذُوقُوا۟ بِمَا نَسِيتُمْ لِقَآءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَآ إِنَّا نَسِينَٰكُمْ ۖ وَذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلْخُلْدِ بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٤﴾
12. Da kuwa za ka ga lokacin da masu manyan laifuka suke sunkuye da kawunansu a wurin Ubangiijnsu (suna cewa): "Ya Ubangijinmu, mun gani, mun kuma ji, to Ka mayar da mu (duniya), za mu yi aiki nagari, haƙiƙa mu masu sakankancewa ne."

13. Idan kuwa da Mun ga dama, tabbas da Mun bai wa kowane rai shiriyarsa, sai dai kuma maganata ta tabbata cewa, tabbas zan cike Jahannama da aljannu da mutane gaba ɗaya.

14. Sai (a ce da su): "Ku ɗanɗani (azaba) saboda mancewa da kuka yi da saduwa da wannan ranar taku, lalle Mu ma Mun yi watsi da ku; kuma ku ɗanɗani azaba mai ɗorewa saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa waɗannan kafiran masu ƙaryata ranar alƙiyama za su bayyana a wannan ranar a gaban Allah cikin halin ƙasƙanci, suna sunkuyar da kawunansu a wulaƙance suna nadama, suna tabbatar wa Ubangiji cewa yanzu kam sun yarda da akwai tashi bayan mutuwa, domin sun gane wa idanuwansu, sun kuma ji maganar gaskiya da aka yi ta faɗa musu ita tun a duniya suna ƙaryatawa. Sai su shiga roƙon Allah cewa ya mayar da su duniya domin su gyara abin da suka ɓata, su yi aiki na ƙwarai, domin su yanzu sun ga dahir; sun tabbatar da gaskiyar abin da manzanninsu suka riƙa gaya musu a duniya. Allah ya bayyana wa Manzonsa cewa da zai ga waɗannan masu manya-manyan laifuffuka a cikin irin wannan hali na ƙasƙanci da nadama to da ya ga babban al'amari mai ban al'ajabi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa komai yana gudana ne da hukuncinsa da ƙaddararsa da cewa, da ya ga dama da lalle kowane rai ya tanadar masa shiriyarsa ya ɗora shi a kan daidaitacciyar hanya, sai dai maganarsa ta riga ta tabbata cewa sai ya cika wutar Jahannama da kafirai na

mutane da aljannu, domin sun zaɓi hanyar kafirci da ɓata a kan hanyar imani da nagarta. Wannan kuwa adalci ne na Allah da gudanar da komai a bisa hikima da dacewa.
Sai kuma ya bayyana cewa za a riƙa faɗa wa su waɗannan ‘yan wuta cewa su ɗanɗani azaba saboda sun manta da haɗuwa da Allah a wannan rana, sun gafala game da ita, don haka Allah zai sanar da su cewa shi ma a wannan rana zai bar su cikin azaba ba tare da ya kula su ba; ya ce da su su ɗanɗani azabar wuta ta dindindin ba mai yankewa ba, saboda abin da suka kasance suna aikatawa a duniya na kafirci da saɓon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar yin tasbihi a cikin salla; a ruku’u ko a sujjada.

2. Munin girman kai da sukar masu girman kai.

3. Falalar sallar dare da addu’a a cikinta.

4. Wajibi ne ga mumini ya zamanto a cikin ibadarsa mai tsoro mai kwaɗayi.

5. Albishir ga muminai waɗanda suka siffantu da siffofin da aka ambata, Allah ya yi musu tanadin abin da babu wani rai da ya san girmansa sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratus Sajda (15-17)
إِنَّمَا يُؤۡمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُواْ بِهَا خَرُّواْ سُجَّدٗا وَسَبَّحُواْ بِحَمۡدِ رَبِّهِمۡ وَهُمۡ لَا يَسۡتَكۡبِرُونَ ١٥ تَتَجَافَىٰ جُنُوبُهُمۡ عَنِ ٱلۡمَضَاجِعِ يَدۡعُونَ رَبَّهُمۡ خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ١٦ فَلَا تَعۡلَمُ نَفۡسٞ مَّآ أُخۡفِيَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعۡيُنٖ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٧

15. Lalle kawai masu imani da ayoyinmu su ne waɗanda idan aka yi musu wa’azi da su za su faɗi suna masu sujjada su kuma yi tasbihi tare da yabon Ubangijinsu, kuma su ba sa yin girman kai.

16. Kuyaɓunsu suna nesantar wuraren kwanciya, suna bauta wa Ubangijinsu cikin halin tsoro da kuma kwaɗayi, kuma suna ciyarwa daga abin da Muka arzuta su.

17. Kuma ba wani rai da zai san abin da aka ɓoye musu na faranta rai, don sakamako game da abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka yi imani da shi da manzanninsa da cewa, masu yin imani da ayoyinsa da ya saukar wa Manzonsa su ne kawai waɗanda idan aka karanta musu waɗannan ayoyi aka yi musu wa’azi da su, sukan faɗi ƙasa suna masu sujjada, su kuma yi tasbihi da yabon Ubangijinsu, ba sa girman kai wajen bautar sa ko yi masa sujjada.
Allah ya bayyana siffofinsu da cewa, suna ƙaurace wa wuraren kwanciya da jikinsu; su haƙura da bacci, su nufi wurin bautar Allah, su tsaya suna salla suna roƙon sa a sallolinsu, suna masu tsoron azabarsa kuma masu kwaɗayin rahamarsa. Suna kuma sadaukar da dukiyoyin da Ubangijinsu ya ba su wajen ɗaukaka addininsa ko taimakon bayinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa babu wani rai da zai san abin da aka tanada musu na sakamako wanda zai faranta musu rai, saboda kyawawan ayyukan da suka aikata a duniya. Sakamako ne da babu wanda ya san iyakar girmansa sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Mu’azu ɗan Jabal (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na yi tafiya tare da Manzon Allah (ﷺ) sai wata rana na wayi gari kusa da shi muna tafiya sai na ce: “Ya Manzon Allah, ka faɗa mini aikin da zai shigar da ni Aljanna, ya nisanta ni daga wuta.” Sai ya ce: “Lalle ka yi tambaya game da wani babban abu, amma kuma mai sauƙi ne ga wanda Allah ya sawwaƙe masa: Ka bauta wa Allah kada ka haɗa komai da shi, ka kuma tsayar da salla, ka kuma bayar da zakka, ka yi azumin Ramadana, ka je hajjin Ɗakin Allah.” Sannan ya ce: “Yanzu ba na nuna maka ƙofofin alheri ba? Azumi garkuwa ne, sadaka kuma tana bice zunubi, da sallar mutum a cikin tsakiyar dare.” Sai ya karanta aya ta 16 har zuwa ta 17…” [Ahmad #22016 da Tirmizi #2616 da Ibn Majah #3973].

An karɓo daga Sahlu ɗan Sa’ad As-Sa’idi ya ce: Na halarci wani majilisi na Manzon Allah (ﷺ) inda ya siffanta Aljanna har ya gama maganarsa. A ƙarshen zancensa sai ya ce: “A cikinta akwai abin da ido bai taɓa gani ba, kunne bai taɓa ji ba, bai kuma taɓa ɗarsuwa a zuciyar wani mutum ba.” Sai ya karanta wannan ayar ta 16 zuwa ta 17. [Muslim #2825].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu daidaito tsakanin mumini da kafiri ko mai biyayya ga Allah da mai aikata saɓon Allah. Don haka ba ƙaramin kuskure ne ba a ce duk mutane daidai suke ba su da bambanci.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan saukar wa al’umma da wata musiba domin su wa’azantu su tuba su dawo kan tafarkin Allah.

3. Bayani a kan cewa babu zaluncin da ya kai na mutumin da za a yi masa wa’azi da ayoyin Allah amma ya bijire musu kamar bai ji su ba ya ci gaba da aika-aikarsa. Lalle wannan sai ya haɗu da fushin Allah idan bai tuba ba.

4. Duk tsananin azabar duniya ba a bakin komai take ba idan an kwatanta ta da azabar lahira.

Suratus Sajda (18-22)

أَفَمَن كَانَ مُؤۡمِنٗا كَمَن كَانَ فَاسِقٗاۚ لَّا يَسۡتَوُۥنَ ١٨ أَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمۡ جَنَّٰتُ ٱلۡمَأۡوَىٰ نُزُلَۢا بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٩ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ فَسَقُواْ فَمَأۡوَىٰهُمُ ٱلنَّارُۖ كُلَّمَآ أَرَادُوٓاْ أَن يَخۡرُجُواْ مِنۡهَآ أُعِيدُواْ فِيهَا وَقِيلَ لَهُمۡ ذُوقُواْ عَذَابَ ٱلنَّارِ ٱلَّذِي كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ٢٠ وَلَنُذِيقَنَّهُم مِّنَ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡأَدۡنَىٰ دُونَ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡأَكۡبَرِ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٢١ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ ثُمَّ أَعۡرَضَ عَنۡهَآۚ إِنَّا مِنَ ٱلۡمُجۡرِمِينَ مُنتَقِمُونَ ٢٢

18. Yanzu wanda ya zamanto mumini ya zama kamar wanda ya kasance fasiƙi? Ai ba za su zama daidai ba.

19. Amma waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, to suna da gidajen Aljanna na makoma, (wannan) liyafa ce saboda abin da suka kasance suna aikatawa.

20. Amma kuma waɗanda suka fice daga biyayyar Allah, to makomarsu wuta ce; ko da yaushe suka yi niyyar fitowa daga gare ta sai a mayar da su a cikinta a kuma ce da su: “Ku ɗanɗani azabar wuta wadda kuka kasance kuna ƙaryatawa.”

21. Kuma tabbas lalle za Mu ɗanɗana musu (wani abu) daga azabar da ta fi ƙanƙanta (ta duniya) kafin azabar da ta fi girma (ta lahira) don su dawo (daga ɓata).

22. Wane ne kuma mafi zalunci fiye da wanda aka yi wa wa’azi da ayoyin Ubangijinsa sannan ya bijire musu? Lalle Mu Masu saka wa masu manyan laifuka ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana babban bambanci da tazara da ke tsakanin mumini da fasiƙi mai bijire wa biyayyar Allah da cewa, babu yadda za a daidaita tsakanin wanda ya yi imani da Allah, ya yi kyawawan ayyuka ya bar abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana da mutumin da ya kauce wa hanyar Allah, ya zaɓi saɓon Allah. Sakamakonsu a wurin Allah ba zai taɓa zama irin ɗaya ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka yi imani da Allah suka yi ayyuka nagari da cewa an tanadar musu Aljanna da za su zauna cikinta cikin karramawa ta Allah gare su, sakamakon kyawawan ayyukan da suka kasance suna yi a duniya.
Sannan kuma ya bayyana sakamakon waɗanda suka kauce wa ɗa’ar Allah suka zaɓi kafirci da saɓon Allah; to su wutar Jahannama ce matabbatarsu da aka tanadar musu a ranar alƙiyama. Duk kuwa lokacin da suka yunƙuro domin su fita daga cikinta sai a mayar da su cikinta, a daka musu tsawa cewa, su ɗanɗani azabar wutar da suka kasance suna ƙaryatawa a duniya lokacin da manzanninsu suke tsorata su da ita.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa waɗannan kafirai cewa, zai ɗanɗana musu azabar duniya ta hanyar jarraba iri-iri da fitintinu da zai saukar musu, kafin su kai ga mafi girman azaba ta lahira idan har suka mutu ba su tuba ba. Ya bayyana cewa yana ɗanɗana musu azabar duniya ne domin ko sa dawo ga ɗa’a ga Allah su tuba su bar abin da suke yi na kafirci.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa babu mafi zalunci kamar wanda aka yi masa wa’azi da ayoyin Allah amma kuma sai ya bijire musu ya yi watsi da su. Sai Allah ya tabbatar da cewa, lalle sai ya yi sakamakon azaba ga masu bijire masa suna aikata kafirci da ayyukan saɓon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da annabcin Annabi (ﷺ) da kuma haɗuwarsa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a daren Isra’i da Mi’iraji.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo ambaton Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a nan, saboda littafinsa da aka saukar masa watau Attaura ya ɗara na kowane annabi cikin annabawan Banu Isra'ila, hakanan shari'arsa babbace, al'ummarsa ma babbar al'umma ce. Matsayinsa a cikin 'ya'yan Isra'ila kamar matsayin Annabi Muhammadu ne (ﷺ) a cikin 'ya'yan Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Duka annabawan Banu Isra'ila da suka zo bayansa sun aiki ne da shari'arsa har shi ma Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shafe kaɗan ne daga cikin hukunce-hukuncen Attaura.

3. Ana samun shugabanci ne na addini ta hanyar siffantuwa da sifar haƙuri da kuma sifar yaƙini da saƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Duk wani saɓani na nan duniya zai zo ƙarshe a ranar alƙiyama yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai yi hukuncinsa na adalci.

Suratus Sajda (23-25)
وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ فَلَا تَكُن فِي مِرۡيَةٖ مِّن لِّقَآئِهِۦۖ وَجَعَلۡنَٰهُ هُدٗى لِّبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٢٣ وَجَعَلۡنَا مِنۡهُمۡ أَئِمَّةٗ يَهۡدُونَ بِأَمۡرِنَا لَمَّا صَبَرُواْۖ وَكَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يُوقِنُونَ ٢٤ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ يَفۡصِلُ بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ٢٥

23. Haƙiƙa kuma Mu Mun bai wa Musa Littafi, to kada ka kasance (kai Manzo) cikin kokwanto na saduwa da shi (Musan). Kuma Mun sanya shi ya zamanto shiriya ga Banu-Isra'ila.

24. Muka kuma sanya shugabanni daga cikinsu waɗanda suke shiryarwa da umarninmu yayin da suka yi haƙuri, suka kuma kasance suna sakankancewa da ayoyinmu.

25. Lalle Ubangijinka Shi ne zai yi hukunci a tsakaninsu ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna sassaɓawa a kansa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci cewa ya ba wa Annabi Musa littafin Attaura, sai kuma ya faɗakar da Manzonsa (ﷺ) cewa, kada ya yi wani kokwanto game da haɗuwarsu da shi Annabi Musa a daren Isra'i da Mi'iraji.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "A daren da aka yi Isra'i da ni na ga Musa ɗan Imrana, wani mutum ne wankan tarwaɗa, dogo mai cibbiri-cibbirin gashin kai kamar dai shi ɗaya ne daga cikin mazajen ƙabilar Shanu'a…" [Bukhari #3239 da Muslim #165].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya sanya littafin Attaura da ya ba wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zama shiriya ne ga Banu Isra'ila, wanda ya ƙunshi shari'ar da ta dace da zamaninsu; saɓanin Alƙur'ani, shi Allah ya sanya shi shiriya ne ga mutanen duniya baki ɗaya a kowane zamani.
Sai kuma Allah ya yaba wa wasu daga cikin Banu Isra'ila, da cewa ya mayar da su shugabanni masu gaskiya waɗanda mutane za su yi koyi da su, suna kuma nuna gaskiya a ayyukansu, saboda haƙurin da suka yi wajen aiki da umarninsa da guje wa haninsa da kuma juriya wajen isar da saƙonsa, sannan kuma suna ba da gaskiya matuƙa sosai da ayoyin da Allah ya saukar wa manzanninsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Manzonsa (ﷺ) cewa shi ne zai yi hukunci a tsakaninsu ranar alƙiyama game da abin da suka kasance a nan duniya suna saɓani a kansa, sai ya bayyana mai gaskiya da marar gaskiya a tsakaninsu ya kuma yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sanin tarihin abin da ya faru ga al'ummun da suka gabata, da yadda Allah ya hallaka waɗanda suka ƙaryata manzanninsa, abu ne da zai taimaka wajen samun shiriya da imani da Allah.

2. Bayanin ni'imar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ke cikin saukar da ruwan sama wanda a sanadiyyarsa ake samun abinci iri-iri; wanda mutane za su ci da wanda dabbobi za su ci. Babu shakka la'akari da wannan babbar ni'imar kaɗai, ya isa ya sa mutane su yi imani da Allah su rungumi shiriyarsa hannu bibbiyu. To amma abin takaici yawancin mutane ba sa la'akari da hakan, suna kallon abin ne kallon al'ada kawai.

Suratus Sajda (26-27)
أَوَ لَمۡ يَهۡدِ لَهُمۡ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا مِن قَبۡلِهِم مِّنَ ٱلۡقُرُونِ يَمۡشُونَ فِي مَسَٰكِنِهِمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٍۖ أَفَلَا يَسۡمَعُونَ ٢٦ أَوَ لَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّا نَسُوقُ ٱلۡمَآءَ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ٱلۡجُرُزِ فَنُخۡرِجُ بِهِۦ زَرۡعٗا تَأۡكُلُ مِنۡهُ أَنۡعَٰمُهُمۡ وَأَنفُسُهُمۡۖ أَفَلَا يُبۡصِرُونَ ٢٧

26. Yanzu ba su gane wa idanunsu ba al'ummu nawa Muka hallakar a gabaninsu waɗanda suke ta zirga-zirga tsakankanin gidajensu? Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi; to me ya sa ba sa sauraro ne?

27. Ko kuwa ba sa gani cewa Mu Muke koro ruwa zuwa ga ƙeƙasasshiyar ƙasa, sai Mu fitar da tsirrai da shi, waɗanda dabbobinsu da su kansu suke ci daga gare shi? To me ya sa ba sa lura ne?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin kafirai a kan cewa yanzu ba su gane wa idanuwansu ba irin yadda Allah ya hallaka al'ummun da suka gabace su waɗanda suka ƙaryata manzanninsu? Ga su kuwa a kullum suna ta zirga-zirga a tsakankanin gidajensu da suke zaune a ciki kafin a hallaka su, amma ba su wa'azantu da wannan ba. Allah ya bayyana cewa lalle a cikin abin da ya faru ga waɗannan al'ummu na hallaka saboda kafircinsu da miyagun ayyukansu akwai abin izina da wa'azi da shaidar da ta tabbatar da cewa manzanninsu masu gaskiya ne, Allah ne kuma ya aiko su. To yanzu su waɗannan kafiran ba za su tsaya su yi sauraro na fahimta da wa'azantuwa ba?
Sannan Allah ya sake jan hankalinsu game da ƙaryata tashi bayan mutuwa da suke yi da cewa, ba sa ganin yadda yake aiko da ruwan sama zuwa ga ƙeƙasasshiyar ƙasa wadda ba ta fitar da komai sai ya raya ta da wannan ruwan saman sai ka ga ta fitar da tsirranta wanda suke ci su da dabbobinsu? Yanzu ashe ba za su dubi wannan aiki na Allah ba su gane cewa wanda ya iya raya ƙeƙasasshiyar ƙasa zai iya raya matattu?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rashin hankalin kafirai da wautarsu da har suke gaggauto wa kawunansu azabar Allah, a madadin su roƙe shi shiriya.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya karɓar tuban bawa yayin da azabar Allah ta nufo shi, ko lokacin da ya ga mala'ikan mutuwa, watau sanda ya zo gargara.

Suratus Sajda (28-30)
وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡفَتۡحُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٢٨ قُلۡ يَوۡمَ ٱلۡفَتۡحِ لَا يَنفَعُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِيمَٰنُهُمۡ وَلَا هُمۡ يُنظَرُونَ ٢٩ فَأَعۡرِضۡ عَنۡهُمۡ وَٱنتَظِرۡ إِنَّهُم مُّنتَظِرُونَ ٣٠

28. Suna kuma cewa: "Yaushe ne (ranar) wannan hukuncin idan kun kasance masu gaskiya?

29. Ka ce: "Ranar hukuncin, waɗanda suka kafirce, imaninsu ba zai amfane su ba, kuma ba ma za a saurara musu ba."

30. To ka rabu da su, ka kuma saurara, lalle su ma masu sauraro ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai suke neman gaggauto da azabar Allah da fushinsa a kansu, domin su nuna rashin imaninsu da Allah har ma suna cewa yaushe ne hukuncin Allah zai zo wanda muminai suke ta faɗa musu cewa yana zuwa, kuma a ranar ne Allah zai yanke hukuncinsa a tsakaninsu ya kai ɗan wuta cikin wuta, ɗan Aljanna ya tafi Aljanna?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) cewa ya faɗa musu, idan ranar hukuncin ta zo, to su sani waɗanda suka kafirce wa Allah a nan duniya, imaninsu ba zai yi musu amfani ba a can yayin da suka yi ido biyu da azabar Allah, kuma ba za a jinkirta musu ba har su tuba a karɓi tubansu.
Sai kuma ya umarci Manzo (ﷺ) cewa ya kau da kansa daga waɗannan kafirai, domin sun riga sun yi zurfi a cikin kafircinsu da ɓatarsu, ya saurari abin da zai auka musu na azaba su ma suna sauraro ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo Annabinsa (ﷺ) da siffar annabta ba kamar yadda yake kiran sauran annabawa da sunayensu ba. Wannan yana nuna girman martabar Manzon Allah (ﷺ) da fifikonsa a kan sauran annabawa, da kuma koyar da al'ummarsa yin ladabi a gare shi yayin ambatonsa, watau kada su kirawo shi da tsurar sunansa babu lafazin girmamawa a ciki, yin haka ba ladabi ne ba.

2. Wajabcin taƙawa, watau aiki da umarnin Allah da guje wa haninsa, domin kare kai daga azabarsa.

3. Nuni a kan cewa babu wani wanda ya fi ƙarfin a yi masa nasiha ko wa'azi, domin ga shi an yi wa Manzon Allah (ﷺ) duk da yawan tsoron Allah da yake da shi.

4. Annabi (ﷺ) bawan Allah ne da aka umarce shi da bin shari'a da riƙo da ita. Don haka babu wani matsayi da bawa zai taka na tsoron Allah har da hukunce-hukuncen shari'a za su sauka daga kansa. Duk wanda yake ganin akwai wani mutum da zai kai matsayin da shari'a za ta sauka daga kansa, to wannan ya ɓata ɓata mabayyani.

5. Haramcin yin biyayya ga kafirai da munafukai da miƙa wuya ga duk wasu buƙatunsu.

6. Wajabcin bin abin da Allah ya saukar na Alƙur'ani da gabatar da shi a kan duk wata fahimta.

7. Gargaɗi da tsoratarwa game da saɓa wa Allah domin Allah masanin duk abin da mutane suke aikatawa ne.

8. Wajabcin dogaro ga Allah shi kaɗai, domin shi ne fiyayyen mai ba da kariya ga bayinsa.

33-Suratul Ahzab

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna '*Suratul Ahzab*'. Ba ta da wani suna sai wannan. *Al-Ahzab* yana nufin gangamin rundunoni. An sa mata wannan suna ne saboda a cikinta ne Allah ya yi bayanin gangamin rundunonin kafiran Kuraishawa da ƙawayensu waɗanda suka nufi yaƙar Musulmi a Madina, amma Allah ya rusa makircinsu, ya tarwatsa su.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun yi ittifaƙi a kan cewa Sura ce *Madaniyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tis'in (90) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta kuma sauka bayan '*Suratul Anfal' kafin 'Suratul Ma'ida'.*

4. Adadin ayoyinta:
Ayoyinta saba'in da uku ne (73) babu wani saɓani.

5. Babban Jigonta:
Wajbacin yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Manzonsa (ﷺ) ɗa'a a ƙowane hali da guje wa saɓa wa umarninsu.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Yawancin ayoyinta suna mayar da martani ne ga munafukai masu faɗar miyagun maganganu game da Manzon Allah da nufin su cutar da shi, kamar maganganunsu a kan aurensa da Zainab 'yar Jahshi.
• Allah ya yi bayanin hukuncin ɗan riƙo da rushe al'adar jahiliyya a kan haka.
• Surar yi magana a kan al'adar Larabawa ta cin gadon juna ta hanyar ƙawance ko hijira, inda aka rushe wannan al'ada.
• Ta yi nuni zuwa ga girman matsayin Annabi (ﷺ) a wurin muminai da cancantarsa gare su fiye da kawunansu.
• Ta kwaɗaitar da muminai a kan su rungumi shari'ar Allah su yi aiki da ita, domin haka shi ne alƙawarin da Allah ya yi da ilahirin annabawansa.
• Bayyana kariyar Allah ga muminai da ba su nasara a kan maƙiyansu waɗanda suka yi gangami domin su ga bayansu.
• Yabo ga muminai a kan gaskiyarsu da jajircewarsu don ba wa addinin Allah kariya.
• Bayanin ni'imar da Allah ya yi wa muminai yayin da ya mallaka musu garuruwan Ahlulkitabi waɗanda suka taimaka wa rundunonin kafirci.
• Bayani a kan hukunce-hukuncen da suka shafi zamantakewar aure na matan Manzon Allah (ﷺ), da bayanin falalarsu da falalar sauran iyalan gidan Manzon Allah (ﷺ) da sauran Musulmi mutanen kirki maza da mata.

• Hukuncin iddar matar da aka saki kafin tarewarta.
• Batu game da matan da suka halatta Annabi (ﷺ) ya aura da kuma hukuncin hijabi ga matansa *Ummahatul Mu'uminina* da suturar 'ya mace Musulma.
• Razanarwa ga munafukai masu yayata ji ta-ji ta a Madina da niyyar tayar wa da Musulmi hankali.
• Kwaɗaitar da Musulmi a kan yawan ambaton Allah da kuma girmama Manzonsa (ﷺ) da yi masa salati.
• Alƙawarin narkon azaba ga munafukai masu cutar da Allah da Manzonsa da muminai.

Ahzab (1-3)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ ٱتَّقِ ٱللَّهَ وَلَا تُطِعِ ٱلْكَٰفِرِينَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمًا ۝١ وَٱتَّبِعْ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا ۝٢ وَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلًا ۝٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya kai wannan Annabi, ka kiyaye dokokin Allah, kada ka yi wa kafirai da munafukai ɗa'a. Lalle Allah Ya kasance Masani ne, Mai hikima.

2. Kuma ka bi abin da ake yi maka wahayinsa daga Ubangijinka. Lalle Allah Ya kasance Masanin abin da kuke aikatawa ne.

3. Ka kuma dogara ga Allah. Allah kuwa Ya isa wakili.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da kira ga Annabi (ﷺ) da umartar sa a kan ya dawwama a kan aiki da umarninsa da guje wa haninsa. Ya kuma hana shi yin biyayya ga kafirai da munafukai a kan abin da zukatansu suke so wanda ya saba wa shari'ar Allah. Allah ya tabbatar da cewa shi masanin duk abin da kafirai da munafukai suke ƙullawa ne, mai hikima ne a halittarsa da tsare-tsarensa da shari'arsa.

Sannan Allah ya umarce shi da bin abin da ya saukar masa na wahayi shi da al'ummarsa, ya tabbatar musu cewa shi masanin duk abin da suke aikatawa ne kuma zai yi musu sakayya a kan ayyukansu baki ɗaya.
Sai kuma ya umarce shi da ya dogara ga Allah shi kaɗai cikin dukkan al'amuransa, domin kuwa shi Allah ya isa ya zamanto wakili mai tsare bayinsa waɗanda suka dogara da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matar da mijinta ya yi mata zihari, watau ya kwatanta ta da mahaifiyarsa wajen haramci, wannan ba zai sa ta zama mahaifiyarsa ba, kuma maganarsa mummunar ƙarya ce

.2. Haramcin aikata zihari, domin idan har Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai sanya matar mutum ta zama mahaifiyarsa ba, to ba ya halatta gare shi ya haɗa abin da Allah bai haɗa ba.

3. 'Ya'yan riƙo ba za su zama daidai da 'ya'yan haƙiƙa a cikin hukunce-hukuncen shari'a ba.

4. Maganar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) gaskiya ce babu ƙarya ko tufka-da-warwara a cikinta, domin gaskiya ba ta warware kanta.

5. Duk da cewa abu ne a bayyane cewa zancen Allah gaskiya ne, to amma ba duk mutane ne suka haɗu a kan bin sa ba sai kawai wanda Allah ya shiryar, domin shi ne kaɗai mai shiryarwa.

6. Wajabcin komawa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wajen neman shiriya.

7. Hanyar gaskiya ɗaya ce, ita ce hanyar Allah.

8. Wajabcin danganta mutum da mahaifinsa na asali, domin kowane mahluƙi mahaifi ɗaya gare shi rak, shi ne wanda ya fito ta tsatsonsa.

9. Halaccin kiran juna da ‘yan’uwantaka ta addini.

10. Ɗauke zunubi daga kan wanda ya aikata laifi bisa kuskure ko rashin sani. Mai zunubi shi ne wanda ya yi laifi da gangan yana sane.

11. Bayanin yalwar rahamar Allah da afuwarsa wadda ta sa ba ya kama bayinsa da laifin kuskure ko rashin sani.

Suratul Ahzab (4-5)
مَّا جَعَلَ ٱللَّهُ لِرَجُلٖ مِّن قَلۡبَيۡنِ فِي جَوۡفِهِۦۚ وَمَا جَعَلَ أَزۡوَٰجَكُمُ ٱلَّٰٓـِٔي تُظَٰهِرُونَ مِنۡهُنَّ أُمَّهَٰتِكُمۡۚ وَمَا جَعَلَ أَدۡعِيَآءَكُمۡ أَبۡنَآءَكُمۡۚ ذَٰلِكُمۡ قَوۡلُكُم بِأَفۡوَٰهِكُمۡۖ وَٱللَّهُ يَقُولُ ٱلۡحَقَّ وَهُوَ يَهۡدِي ٱلسَّبِيلَ ٤ ٱدۡعُوهُمۡ لِأٓبَآئِهِمۡ هُوَ أَقۡسَطُ عِندَ ٱللَّهِۚ فَإِن لَّمۡ تَعۡلَمُوٓاْ ءَابَآءَهُمۡ فَإِخۡوَٰنُكُمۡ فِي ٱلدِّينِ وَمَوَٰلِيكُمۡۚ وَلَيۡسَ عَلَيۡكُمۡ جُنَاحٞ فِيمَآ أَخۡطَأۡتُم بِهِۦ وَلَٰكِن مَّا تَعَمَّدَتۡ قُلُوبُكُمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمًا ٥

4. Allah bai sanya wa wani mutum zuciya biyu ba a cikinsa. Kuma bai sanya matanku waɗanda kuke yi musu zihari (su zama) iyayenku ba. Bai kuma sanya ‘ya’yan riƙonku (su zama) ‘ya’yanku ba. Wannan magana ce da kuke yi da bakunanku; Allah kuwa Yana faɗar gaskiya ne, kuma Shi ne Yake shiryarwa ga hanya (ta gaskiya).

5. Ku danganta su (‘ya’yan riƙo) ga iyayensu maza shi ne adalci a wurin Allah. Amma idan ba ku san iyayensu maza ba, to ‘yan’uwanku ne a addini, kuma bararrun bayinku ne. Babu kuma laifi a kanku game da abin da kuka yi kuskuren yin sa, sai dai abin da zukatanku suka yi gangancin (aikatawa). Allah kuwa Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda aka riga aka sani cewa, babu wani mutum da Allah ya halicce shi da zuciya biyu a jikinsa; kowane mahaluƙi da zuciya ɗaya aka san shi. Don haka ba yadda za a yi matar mutum ta zama mahaifiyarsa; kowa a duniya mahaifiya ɗaya gare shi, ita ce wadda ta tsuguna ta haife shi. To duk wanda ya haramta wa kansa matarsa saboda ya mayar da ita a matsayin mahaifiyarsa, wannan ya zo da ƙarya da mummunar magana. Hakanan kuma ‘ya’yan riƙo da suke ƙarƙashin wasu ba za su taba zama ‘ya’yansu na cikinsu ba, su zama daidai wajen hukunce-hukuncen shari’a, domin ɗan mutum na haƙiƙa shi ne wanda ya haife shi daga tsatsonsa.
Da wannan bayani ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rushe al’adar nan ta Larabawa ta jahiliyya da mutum yake haramta wa kansa matarsa ta hanyar kwatanta ta da mahaifiyarsa. Hakanan kuma al’adarsu ta mayar da ‘ya’yan riƙo daidai da ‘ya’yan da suka haifa wajen hukunce-hukuncen auratayya da gado. Allah ya tabbatar musu da cewa wannan magana ce kawai da suke faɗa da bakunansu, amma ko kaɗan ba gaskiya ce ba. Allah shi ne mai faɗar gaskiya don bayinsa su ji su yi aiki da ita, kuma shi ne yake shiryar da su zuwa ga hanyar gaskiya.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su danganta ‘ya’yan riƙo ga iyayensu maza na haƙiƙa, domin yin haka ne kaɗai adalci a wurin Allah. Idan kuwa ba su san iyayensu maza ba, to su riƙe su a matsayin ‘yan’uwansu ne a addini. Kuma ‘yantattun bayinsu, su ce da ɗayansu: Ya ɗan’uwana, wannan babu laifi a cikinsa. Hakanan idan sun yi kuskure wajen danganta wani zuwa wanda ba mahaifinsa ba, to a nan ma ba su da laifi. Amma za a kama su da laifi yayin da suka yi gangancin danganta wani zuwa wanda ba shi ya haife shi ba. Idan bawa ya yi laifi sannan ya tuba to lalle Allah mai gafara ne zai karɓi tubarsa, mai jin ƙai ne, shi ya sa ba zai kama mutum da laifin kuskure ba.
Wannan ayar ta shafe abin da yake a farkon Musulunci na halaccin dangata ‘ya’yan riƙo zuwa ga waɗanda suke riƙon su. Allah ya yi umarni da cewa, lalle kowa a danganta shi da mahaifinsa na asali, yin haka kuma shi ne adalci a wurinsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: A da can Zaidu ɗan Harisa ba ma kiran sa da wani suna sai Zaidu ɗan Muhammad saboda shi ne ya ‘yanta shi, har sai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: ‘Ku danganta su ga iyayensu maza shi ya fi adalci a wurin Allah.’ [Bukhari #4782 da Muslim #2425].

An karɓo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: “Abu Huzaifa ɗan Utbatu ɗan Rabi’a sahabi ne da ya halarci yaƙin Badar, ya mayar da ɗan riƙonsa Salim ɗansa, ya kuma aura masa ‘yar ɗan’uwansa, watau Hindatu ‘yar Walidu ɗan Utbatu, alhalin shi Salim bararren bawa ne na wata mace daga cikin mutanen Madina. Hakanan Manzon Allah (ﷺ) ya mayar da Zaidu ɗansa. Yadda kuma abin yake tun a zamanin jahiliyya, idan mutum ya mayar da ɗan riƙonsa ɗansa sai mutane su danganta masa shi, idan ya mutu kuma sai wannan ɗan riƙo ya ci gadonsa, har lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar. Sai aka danganta su zuwa iyayensu maza na asali; wanda kuwa ba a san ubansa ba sai akan ɗauke shi ɗan’uwa ko bararren bawa…” [Bukhari #4000].
Babu laifi don wani ya kira ɗan wani da cewa ‘ya ɗana’ da nufin nuna ƙauna da soyayya a gare shi.

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Manzon Allah (ﷺ) ya ce mini: ‘Ya ɗana.’” [Muslim #2151].

An karɓo daga Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wanda ya danganta kansa ga wanda ba babansa ba alhali yana sane da cewa ba shi ne babansa ba, to Aljanna ta haramta gare shi.” [Bukhari #6766 da Muslim #63].

An karɓo daga Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: ‘Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “…wanda ya danganta kansa ga wanda ba babansa ba; ko ya dangantu ga waɗanda ba su ne suka ‘yanta shi ba, to la’anar Allah da ta mala’iku da mutane gaba ɗaya ta tabbata a kansa, Allah ba zai karɓi farillarsa ko nafila ba.” [Muslim #1370]

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Fifita son Manzon Allah (ﷺ) a kan komai da fifita maganganunsa a kan maganar kowa, domin ya fi kowa tausayin wannan al’umma, amfaninsa ya shafi kowa da kowa; duk wani alheri da wannan al’umma take ciki a sanadiyyarsa ne, don haka ne idan muradinsa ya ci karo da muradin zuciyar mumini to lalle ya yi watsi da muradin zuciyarsa ya bi muradin Manzon Allah (ﷺ), ya kuma fifita shi a kan iyayensa da ‘ya’yansa da iyalansa da duk mutane baki ɗaya.

2. Dukkan matan Annabi (ﷺ) iyaye ne ga muminai. Duk wanda ya ƙi wata daga cikinsu to ya fitar da kansa daga sahun muminai, domin da yana cikinsu da ya yarda uwa take gare shi, kuma babu yadda za a yi ɗa ya ƙi uwarsa.

3. Haramcin auren matan Manzon Allah (ﷺ) saboda kasancewarsu iyayen muminai.

4. Falalar hijira da martabarta.

5. Tabbatar gado ga dangi na zumunci. Ɗan'uwa na zumunci kuwa shi ne duk wani makusanci wanda ba shi da kason gado kuma ba ya asibci.

6. An riga an rubuta komai a cikin Lauhul Mahfuzu.

Suratul Ahzab (6)
ٱلنَّبِيُّ أَوۡلَىٰ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ مِنۡ أَنفُسِهِمۡۖ وَأَزۡوَٰجُهُۥٓ أُمَّهَٰتُهُمۡۗ وَأُوْلُواْ ٱلۡأَرۡحَامِ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلَىٰ بِبَعۡضٖ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ إِلَّآ أَن تَفۡعَلُوٓاْ إِلَىٰٓ أَوۡلِيَآئِكُم مَّعۡرُوفٗاۚ كَانَ ذَٰلِكَ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مَسۡطُورٗا ٦

6. Annabi shi ya fi cancanta ga muminai fiye da kansu; matansa kuma iyayensu ne. Dangi na zumunta kuma shashinsu ya fi kusanci daga wani shashi a cikin Littafin Allah daga kusancin muminai da masu hijira, sai dai idan za ku aikata wani alheri ne ga masoyanku (muminai). Wannan ya kasance a rubuce a cikin Lauhul Mahafuzu.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa Annabi Muhammadu (ﷺ) shi ne ya fi cancantar su yi wa biyayya, su nuna masa ƙauna a fili fiye da kawunansu, su kuma fifita abin da ya umarce su da shi a kan abin da zukatansu suke sha'awa. Matansa kuwa a matsayin iyayen muminai suke a wajen girmamawa da darajtawa, don haka haramun ne ga wani mumini ya auri ɗaya daga cikinsu bayan rasuwarsa (ﷺ).

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani mumini face ni na fi kowa cancantar ya yi mini biyayya a duniya da lahira. Ku karanta wannan ayar in kun ga dama: 'Annabi shi ya fi cancanta da muminai (su yi masa biyayya) fiye da kawunansu.' Duk muminin da ya mutu ya bar dukiya to magadansa su gaje shi ko su wane ne. Idan kuwa ya bar bashi ko iyali mabuƙata, to waliyyinsa ya zo wurina ni ne majiɓincin al'amarinsa." [Bukhari #2399].

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ni ne na fi cancanta ga kowane mumini fiye da kansa, duk mutumin da ya mutu ya bar bashi, to a zo wurina, wanda kuwa ya bar dukiya to ta magadansa ce." [Muslim #867].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Hisham (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Na kasance tare da Annabi (ﷺ) yana riƙe da hannun Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) sai Umar ya ce masa: 'Ya Manzon Allah, lalle na fi son ka fiye da komai in ban da raina.' Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce da shi: "A'a, na rantse da wanda raina yake hannunsa, har sai ka fi so na fiye da ranka." Sai Umar ya ce da shi: "To lalle kam yanzu wallahi na fi son ka fiye da raina." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: 'Sai yanzu ne ya Umar.'" [Bukhari #6632].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuma bayyana wa muminai cewa dangi na zumunci su ne suka fi cancanta su ci gadon junansu a cikin hukuncin da Allah ya zartar, fiye da sauran muminai da waɗanda suka yi hijira

don Allah. Waɗanda a farkon Musulunci suke cin gadon junansu ta wannan hanyar, sai aka soke gado a tsakaninsu daga baya. Sai kuma Allah ya nuna musu cewa suna iya su kyautata wa ‘yan’uwansu muminai waɗanda ba za su ci gadonsu ba, ta hanyar wasiyya ko kyauta; yin haka abu ne mai kyau. Ya tabbatar musu da cewa wannan hukunci da ya bayyana musu haka yake a rubuce a cikin Lauhul Mahfuzu, don haka aiki da shi ya zama wajibi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nauyin da Allah ya ɗora wa annabawa na isar da saƙonsa ga al’ummunsu nauyi ne mai girma, don haka su ma magadansu malamai nauyin da ke kansu ba ƙarami ne ba.

2. Fifikon waɗannan annabawa biyar a kan sauran annabawa, don haka aka ambace su a keɓe bayan an ambaci sauran annabawa a dunƙule.

3. Annabi Muhammadu (ﷺ) shi ne mafificin annabawa, don haka aka fara ambatonsa duk kuwa da cewa shi ne na ƙarshen zuwa.

4. Ba kafirai da masu laifi ne kaɗai za a yi wa tambayoyi a lahira ba, har ma da masu gaskiya, kamar annabawa da salihai.

5. Tabbatar da tashi bayan mutuwa da sakamakon ranar lahira da kuma tabbatar da samuwar wutar Jahannama a halin yanzu.

Suratul Ahzab (7-8)
وَإِذۡ أَخَذۡنَا مِنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِيثَٰقَهُمۡ وَمِنكَ وَمِن نُّوحٖ وَإِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَى ٱبۡنِ مَرۡيَمَۖ وَأَخَذۡنَا مِنۡهُم مِّيثَٰقًا غَلِيظٗا ٧ لِّيَسۡـَٔلَ ٱلصَّٰدِقِينَ عَن صِدۡقِهِمۡۚ وَأَعَدَّ لِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابًا أَلِيمَۢا ٨

7. Kuma (ka tuna) lokacin da Muka riƙi alƙawura daga annabawa (na isar da aike), kuma daga gare ka, kuma daga Nuhu da Ibrahimu da Musa da Isa ɗan Maryamu; Muka kuma riƙi alƙawari mai kauri daga gare su.

8. Don (Allah) Ya tambayi masu gaskiya game da gaskiyarsu, Ya kuma tanadi azaba mai raɗaɗi ga kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya tuna alƙawari mai ƙarfi da ya yi da annabawa na cewa su bauta masa shi kaɗai kada su haɗa shi da komai, kuma su isar wa al’ummunsu wahayin da ya yi musu. Sai kuma Allah ya ware manyansu waɗanda suka fi himma wajen isar da saƙonsa, ya tuna musu alƙawarinsa a gare su, waɗannan kuwa su ne: Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) da kuma Annabi Nuhu wanda shi ne farkon manzannin Allah a bayan ƙasa, sai kuma Annabi Ibrahim Badaɗayin Allah mai rahama, uban annabawa, sannan Annabi Musa abokin zancen Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sannan Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) mai yawan albarka. Allah ya tabbatar wa da Annabi (ﷺ) shugaban talikai duka, cewa ya yi alƙawari mai ƙarfi da waɗannan annabawa duka.
Ya yi wannan alƙawari ne da su domin ya tambayi masu gaskiya game da gaskiyarsu, ya kuma tambayi annabawan ko sun isar da saƙon da ya aike su da shi, domin ya yi kyakkyawar sakayya ga waɗanda suka ba da gaskiya da su suka bi su; su kuma waɗanda suka kafirce musu suka ƙaryata saƙon da ya aiko su da shi ya yi musu tanadin wata azaba mai raɗaɗi ta wutar Jahannama a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin babbar ni'imar da Allah ya yi wa wannan al'umma da kariyar da ya ba wa muminan farko, watau Annabi (ﷺ) da sahabbansa, don haka ya umarce su su riƙa tunawa da wannan ni'imar da ya yi musu su kuma gode masa.

2. Tsananin ƙiyayyar da take tsakanin kafirai da Musulmi wadda har ta sanya suka haɗa kai suka yi wannan gangamin, duk da cewa ba kowace ƙabila ce daga cikinsu take da alaƙa da 'yar'uwarta ba; babu abin da ya haɗa kansu sai gaba da ƙiyayya ga Musulmi.

3. Bayanin cikakkiyar Kudurar Allah yayin da ya aiko wa kafirai rundunar iska ta fasa taronsu.

4. Bayanin cewa mala'iku rundunar Allah ce suna ba wa muminai kariya. Allah mawadaci ne, ba shi da buƙatar komai a wurin wani.

5. Mutane ba sa ganin mala'iku a kamanninsu na asali, amma suna iya ganin su a kamannin mutane kamar yadda sahabbai suka ga Mala'ika Jibrilu a cikin kamannin Balaraben ƙauye.

6. Al'amarin da ya sami Musulmi a yaƙin Gwalalo babban al'amari ne wanda ya jefa su cikin firgici da tsoro da tashin hankali. Wannan shi yake ƙara fito da girman ni'imar da Allah ya yi musu yayin da ya ba su kariya, ya kuma karya abokan gabarsu.

7. Mutum ya ji tsoron wani abu tsoro na ɗabi'a ba a kiran sa shirka, kuma ba a zargin mutum a kansa.

8. Duk da girman martabar da sahabbai suke da ita a wurin Allah, wannan bai hana su faɗawa cikin wasu zace-zace ba yayin da al'amari ya tsananta, sai dai irin waɗannan zace-zace sukan gushe musu da gaggawa da zarar sun tuna alƙawarin da Allah ya yi musu na samun nasara a kan maƙiyansu.

Suratul Ahzab (9-11)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَةَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ إِذۡ جَآءَتۡكُمۡ جُنُودٞ فَأَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ رِيحٗا وَجُنُودٗا لَّمۡ تَرَوۡهَاۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرًا ٩ إِذۡ جَآءُوكُم مِّن فَوۡقِكُمۡ وَمِنۡ أَسۡفَلَ مِنكُمۡ وَإِذۡ زَاغَتِ ٱلۡأَبۡصَٰرُ وَبَلَغَتِ ٱلۡقُلُوبُ ٱلۡحَنَاجِرَ وَتَظُنُّونَ بِٱللَّهِ ٱلظُّنُونَا ١٠ هُنَالِكَ ٱبۡتُلِيَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَزُلۡزِلُواْ زِلۡزَالٗا شَدِيدٗا ١١

9. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku tuna ni'imar Allah a gare ku lokacin da wasu rundunoni (na gangankon kafurai) suka zo muku, sai Muka aiko musu iska da wasu rundunoni da ba ku gan su ba. Allah kuwa Ya kasance Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

10. A lokacin da suka zo muku ta samanku da ƙasanku, da kuma yayin da idanuwa suka kauce wa (ganin komai sai maƙiya), zukatanku kuma suka cika da tsoro kuka riƙa zace-zace game da Allah.

11. A nan ne fa aka jarrabi muminai, aka kuma girgiza su girgizawa mai tsanani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin wata babbar ni'ima da ya yi wa Musulmi ta ba su kariya da nasara a kan gangamin abokan gabarsu, ya kuma ja hankalinsu zuwa ga yi masa godiya a kan wannan ni'imar.

Kafiran Kuraishawa sun yi ta kwafsa yaƙi da Musulmi amma ba su sami wata nasara ba, sun jefa kansu cikin matsaloli da dama har ta kai kasuwancinsu ya shiga matsala, domin sun rasa hanyoyinsu na tafiya ƙasar Sham fatauci. Hakanan su ma Yahudawan Madina sun gwada yaƙar Manzon Allah (ﷺ) ta hanyoyin makirce-makirce amma ba su yi nasara ba, har Annabi (ﷺ) ya kori wasu daga cikinsu daga Madina. Wannan ya sa suka shiga zuga mushirikai a kan su haɗa ƙarfi su yaƙi Musulmi don su karya su su huta. A shekara ta biyar bayan hijira suka haɗa runduna ta mayaƙa dubu goma suka nufo Madina don rushe da'awar Annabi (ﷺ) da kawo ƙarshen Musulunci.
Da Annabi (ﷺ) ya samu labarin kafirai za su zo yaƙar sa, sai ya yi shawara da sahabbansa a kan abin da ya kamata su yi don fuskantar wannan babbar matsala, sai suka yanke shawara a kan su haƙa rami babba, watau Gwalalo a kan iyakokin Madina domin hana rundunonin kafirai shigowa cikinta, saboda sun yi yawan da Musulmi ba za su iya tunkarar su da yaƙi ba.
To a nan ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake tunatar da Musulmi game da ni'imar da ya yi musu, da cewa rundunonin kafirai sun zo Madina domin yaƙar su inda Yahudawan Madina da munafukai suka taimaka wa kafiran, to amma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da wata iska mai ƙarfi wadda ta tuttunɓuke tantunansu, ta kifar da tukwanen girke-girkensu, ta kashe musu wutacen da suka hura, kuma guguwa mai ƙarfi ta taso ta turbuɗe musu kayayyakinsu, nan take duk suka ɗaiɗaice cikin hasara da wulaƙanci. Allah kuma ya aiko musu da wata runduna ta mala'iku waɗanda babu mai ganin su, Allah kuma ya kasance mai ganin abin da bayinsa suke aikatawa ne, kuma zai yi musu sakayya a kan ayyukansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin tsananin tsoro da Musulmi suka shiga yayin da kafirai suka zo musu ta saman kwazazzabo da ƙasansa, watau ta gabas da yamma, a lokacin idanu suka kauce wa ganin komai in ban da maƙiyansu, zukata suka cika da tsoro da razani har wasu daga cikin Musulmi suka yi ta yin zace-zace iri-iri game da Allah; wani lokaci su yi zaton samun nasara, wani lokaci kuma su riƙa zaton ba za su yi nasara ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a wannan lokaci ne aka jarrabi muminai da ganin wannan gangami na maƙiya, aka kuma girgiza su da tsananin tsoro matuƙar girgizawa, a lokacin ne aka gane mumini na gaskiya da munafuki mai ƙaryar imani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jan hankalin Musulmi da su yi taka-tsantsan da munafukai domin ba mutane ne da ake sakin jiki da su ba, saboda duk lokacin da suka sami wata dama da za su cutar da Musulmi to za su yi amfani da ita.

2. Cutuka iri biyu ne, akwai cutar jiki akwai kuma ta zuciya. Cutar zukata ta fi ta jiki haɗari nesa ba kusa ba, kuma mutum mai hankali shi ne wanda ya fi kulawa da lafiyar zuciyarsa a kan lafiyar jikinsa.

3. Tawayen munafukai ga Manzon Allah (ﷺ) yayin da suka ƙi kiran Musulmi da sunansu na Musulmi ko muminai sai suka kira su da sunan 'Mutanen Yasriba', watau suka bijire wa sunan da Manzon Allah (ﷺ) ya sanya wa Madina, suka koma suna kiran ta da tsohon sunanta na jahiliyya, watau Yasriba.

4. Duk wanda zai yi kira a kan a yi watsi da gaskiya to wannan ya fi kama da munafukai.

5. Karya siffa ce ta munafukai, don haka ne suka riƙa cewa gidajensu fayau suke ba su da tsaro, alhalin kuwa ƙarya suke yi.

6. Munafuki mutum ne wanda ba shi da wata manufa ta kirki a rayuwarsa ta duniya, shi dai buƙatarsa kawai ya more rayuwarsa a sunan Musulunci ko a kafirci bai damu ba.

7. Munafukai mutane ne masu cin amana da yawan yaudara, don haka duk wanda yake mayaudari maci amana to ya ɗauki halayen munafukai ne.

8. Haramcin juya baya a gudu daga fagen daga ba tare da wani uzuri na shari'a ba, kuma yin haka babban laifi ne a wurin Allah.

9. Tabbatar da hisabi a ranar alƙiyama, duk wani alƙawari ko yarjejeniya abin tambayar bawa ne a ranar alƙiyama.

10. Babu mai iya guje wa ƙaddarar Allah.

11. Duk tsawon zaman mutum a duniya ɗan lokaci ne ƙanƙani.

12. Munafukai mutane ne matsorata wulaƙantattu.

13. Babu wani mai hana faruwar abin da Allah ya yi nufi.

Suratul Ahzab (12-17)

وَإِذۡ يَقُولُ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ مَّا وَعَدَنَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ إِلَّا غُرُورٗا ١٢ وَإِذۡ قَالَت طَّآئِفَةٞ مِّنۡهُمۡ يَٰٓأَهۡلَ يَثۡرِبَ لَا مُقَامَ لَكُمۡ فَٱرۡجِعُواْۚ وَيَسۡتَـٔۡذِنُ فَرِيقٞ مِّنۡهُمُ ٱلنَّبِيَّ يَقُولُونَ إِنَّ بُيُوتَنَا عَوۡرَةٞ وَمَا هِيَ بِعَوۡرَةٍۖ إِن يُرِيدُونَ إِلَّا فِرَارٗا ١٣ وَلَوۡ دُخِلَتۡ عَلَيۡهِم مِّنۡ أَقۡطَارِهَا ثُمَّ سُئِلُواْ ٱلۡفِتۡنَةَ لَأٓتَوۡهَا وَمَا تَلَبَّثُواْ بِهَآ إِلَّا يَسِيرٗا ١٤ وَلَقَدۡ كَانُواْ عَٰهَدُواْ ٱللَّهَ مِن قَبۡلُ لَا يُوَلُّونَ ٱلۡأَدۡبَٰرَۚ وَكَانَ عَهۡدُ ٱللَّهِ مَسۡـُٔولٗا ١٥ قُل لَّن يَنفَعَكُمُ ٱلۡفِرَارُ إِن فَرَرۡتُم مِّنَ ٱلۡمَوۡتِ أَوِ ٱلۡقَتۡلِ وَإِذٗا لَّا تُمَتَّعُونَ إِلَّا قَلِيلٗا ١٦ قُلۡ مَن ذَا ٱلَّذِي يَعۡصِمُكُم مِّنَ ٱللَّهِ إِنۡ أَرَادَ بِكُمۡ سُوٓءًا أَوۡ أَرَادَ بِكُمۡ رَحۡمَةٗۚ وَلَا يَجِدُونَ لَهُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ١٧

12. Kuma (ka tuna) lokacin da munafukai da waɗanda suke da cuta a zukatansu suke cewa: "Allah da Manzonsa ba wani alƙawarin da suka yi mana sai na ruɗi."

13. Kuma (ka tuna) lokacin da wata jama'a daga cikinsu ta ce: "Ya ku mutanen Yasriba, ba ku da wurin zama, sai ku koma." Wata ƙungiya kuma daga cikinsu tana neman izinin Annabi da cewa: "Lalle gidajenmu tsirara tuƙwi suke," alhali kuwa ba tsirara tuƙwi suke ba; ba abin da suke nufi sai gudu.

14. Da kuwa za a shigo musu ta kowane ɓangare sannan a neme su da yin fitinar (komawa ga kafirci), to Wallahi da sun aikata (hakan) ba kuwa za su jinkirta da shi ba (wato kafircin) sai ɗan lokacin ƙanƙani.

15. Tun da can kuwa haƙiƙa sun yi wa Allah alƙawarin (cewa) ba za su ba da baya ba. Alƙawarin Allah kuwa ya kasance abin tambaya ne.

16. Ka ce: "In kuna guje wa mutuwa ne ko kisa, to gudun ba zai amfane ku ba, a yayin nan kuwa ba za a jiyar da ku wani daɗi ba sai ɗan kaɗan."

17. Ka ce: "Wane ne zai kare ku daga Allah idan Ya nufe ku da wani mummunan abu ko kuma Ya nufe ku da wata rahama?" Ba kuma za su sama wa kansu wani majiɓinci ko mai taimako ba in ba Allah ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin da munafukai suka riƙa nuna wa Musulmi yayin da suka ga yanayin da Musulmi suke ciki, inda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ)

ya tuna sanda munafukai da wasu masu raunin imani masu shakka a zukatansu suke da'awar cewa duk alƙawarin nasara a kan maƙiya wanda Allah da Manzonsa suka yi musu ba komai ne ba sai ruɗi kawai, watau ruɗar su kawai ake yi ba a gaya musu gaskiyar al'amari. An ruwaito cewa wani daga cikin munafukai har cewa yake yi: "Muhammadu yana yi mana alƙawarin cewa za mu mallake taskokin dukiyar Kisra da Kaisara, alhalin ga shi ɗayanmu ba ya iya fita bayan gari don biyan buƙatarsa." [Dubi, Ɗabarani Al-*Mu'jamul Kabir* #3017].

Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar Manzonsa (ﷺ) da cewa ya tuna lokacin da wata ƙungiya ta munafukai suka riƙa kiran muminai mutanen Madina da sunan 'Mutanen Yasriba', watau tsohon sunan Madina tun gabanin Musulunci, suna cewa ba su da wurin zama a inda suka tsaya, watau daidai dutsen *Sal'u* a kusa da Gwalalon da suka haƙa, suna umartar su da su koma gidajensu cikin ƙuryar Madina, suna kuwa faɗa musu haka ne domin su daƙile su su hana su yaƙi tare da Manzon Allah (ﷺ) da sauran Musulmi mutanen Makka.
Sai kuma wata ƙungiyar daban ta munafukai waɗanda su kuma suka riƙa neman izinin Annabi (ﷺ) a kan ya ba su dama su koma gidajensu, suna da'awar cewa sun baro gidajensu fayau babu wani tsaro, don haka suna jin tsoron kada abokan gabarsu su auka wa iyalansu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaryata su ya tabbatar wa Manzon Allah cewa gidajensu ba fayau suke ba kamar yadda suka faɗa; manufarsu kawai ita ce su gudu su bar fagen yaƙi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara fito da halin waɗannan munafukai fili da cewa, da a ce kafirai za su sami shigo musu cikin Madina ta kowace nahiya sannan su neme su da su bar Musulunci su koma cikin kafirci da shirka da Allah, ba shakka da sun yarda sun ba wa maƙiyansu wannan dama sun yi ridda sun koma cikin shirka, ba tare da sun jinkirta aikata hakan ba sai jinkiri na ɗan lokaci kaɗan, domin da man addinin bai ratsa zukatansu ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara da cewa da can su waɗannan munafukai bayan gudowar ranar yaƙin Uhudu sun yi wa Allah alƙawari ba za su sake gudu daga fagen yaƙi ba domin tsoro ko karya alƙawari, to sai ga shi yanzu sun karya wannan alƙawarin sun manta da cewa sai Allah ya tambayi bawansa a kan alƙawarin da ya ɗauka, shin ya cika koko a'a?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya faɗa wa munafukai cewa gudu daga fagen daga don tsoron yaƙi ko tsoron mutuwa ba zai yi musu wani amfani ba, domin Allah ya riga ya yanka wa kowa ajalinsa, don haka ko da sun gudu amma ajalinsu bai yi ba, to fa ba za su ji daɗin rayuwarsu ba sai na ɗan lokaci kaɗan.
Sai Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya tambaye su cewa wane ne ya isa ya kare su daga Allah idan ya nufe su da wani mummunan abu kamar mutuwa ko kisa, ko kuma ya nufe su da wata rahama kamar kuɓuta daga kisa ko samun wani alheri, wane ne zai iya hana ɗayan waɗannan ya same su? Don haka gudunsu daga fagen yaƙi ba zai tsinana musu komai ba, kuma ba za su iya sama wa kansu wani majiɓincin al'amarinsu ko mataimaki ba wanda zai kare su daga azabar Allah in ba Allah shi kaɗai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kewaye komai, duk ƙanƙantar abu ko girmansa ko zurfinsa Allah yana sane da shi. Hakanan yana sane da duk abin da zai faru nan gaba.

2. Ragwancin munafukai da rashin iya taɓuka komai a lokacin yaƙi.

3. Tsananin rowa wata siffa ce daga siffofin munafukai.

4. Munafukai mutane ne masu tsananin tsoron mutuwa, domin suna da matsananciyar ƙaunar rayuwar duniya.

5. Ishara a kan cewa mutuwa tana da magagi da maye.

6. Mummunan halin munafukai na faɗa wa muminai baƙaƙen maganganu da kausasan lafuzza a lokacin da ake zaune lafiya babu wani tashin hankali.

7. Munafukai ba muminai ne na gaskiya ba.

8. Kafirci na sarari da na ɓoye yana lalata aiki.

9. Da munafiki zai fita yaƙi tare da muminai, to ba zai taɓuka wani abin kirki ba sai dai ya yi yaƙin domin riya.

Suratul Ahzab

(18-20)

*قَدۡ يَعۡلَمُ ٱللَّهُ ٱلۡمُعَوِّقِينَ مِنكُمۡ وَٱلۡقَآئِلِينَ لِإِخۡوَٰنِهِمۡ هَلُمَّ إِلَيۡنَاۖ وَلَا يَأۡتُونَ ٱلۡبَأۡسَ إِلَّا قَلِيلًا ١٨ أَشِحَّةً عَلَيۡكُمۡۖ فَإِذَا جَآءَ ٱلۡخَوۡفُ رَأَيۡتَهُمۡ يَنظُرُونَ إِلَيۡكَ تَدُورُ أَعۡيُنُهُمۡ كَٱلَّذِي يُغۡشَىٰ عَلَيۡهِ مِنَ ٱلۡمَوۡتِۖ فَإِذَا ذَهَبَ ٱلۡخَوۡفُ سَلَقُوكُم بِأَلۡسِنَةٍ حِدَادٍ أَشِحَّةً عَلَى ٱلۡخَيۡرِۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَمۡ يُؤۡمِنُواْ فَأَحۡبَطَ ٱللَّهُ أَعۡمَٰلَهُمۡۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرًا ١٩ يَحۡسَبُونَ ٱلۡأَحۡزَابَ لَمۡ يَذۡهَبُواْۖ وَإِن يَأۡتِ ٱلۡأَحۡزَابُ يَوَدُّواْ لَوۡ أَنَّهُم بَادُونَ فِي ٱلۡأَعۡرَابِ يَسۡـَٔلُونَ عَنۡ أَنۢبَآئِكُمۡۖ وَلَوۡ كَانُواْ فِيكُم مَّا قَٰتَلُوٓاْ إِلَّا قَلِيلًا ٢٠

18. Haƙiƙa Allah Yana sane da masu hana ruwa gudu daga cikinku, da masu ce wa ‘yan’uwansu: “Ku zo wurinmu,” kuma ba sa zuwa yaƙi sai kaɗan.

19. (Su ne) masu yi muku rowar (taimako); sannan idan (abin) tsoro ya zo, sai ka gan su suna duban ka idanuwansu suna jujjuyawa kamar wanda yake suman mutuwa; sannan idan tsoron ya yaye, sai su riƙa cutar da ku da harsuna kaifafa, suna masu rowar alheri. Waɗannan ba su yi imani ba, don haka Allah Ya lalata ayyukansu. Wannan kuwa ya kasance abu ne mai sauƙi a wurin Allah.

20. Suna zaton rundunonin gangami ba su tafi ba; da a ce kuwa rundunonin na gangami za su sake dawowa to da sai su riƙa burin ina ma suna can tare da mutanen ƙauye suna tambayar labaranku; ko ma da za su kasance a cikinku to da ba za su yi yaƙi ba sai ɗan kaɗan.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tabbatar da cewa yana sane da duk abin da munafukai suke yi na daƙile Musulmai da karya musu gwiwa wajen fita yaƙi, yana kuma sane da masu cewa ‘yan’uwansu su dawo wurinsu su bar fagen yaƙi domin babu wata nasara da za su samu a can, kuma suna jiye musu tsoron a kashe su. Allah ya bayyana cewa waɗannan masu sage wa ‘yan’uwansu gwiwa mutane ne da ba kasafai suke fita yaƙi tare da Musulmi ba sai wasu ‘yan lokuta kaɗan, domin kawai guje wa abin kunya ba don su taimaka wa Allah da Manzonsa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana wani mummunan hali da aka san munafukai da shi na tsananin rowa da dukiyarsu ba sa ciyar da ita don Allah, kuma masu rowa da kawunansu ba sa fita yaƙi tare da Musulmi sannan ba sa nuna wa Musulmi ƙauna ko kaɗan.
Sannan kuma ya bayyana tsananin tsoro da ke tare da su da zarar sun ga wani abin tsoro, kamar abokan gaba sun tunkaro su sai a gan su sun yi zuru-zuru da idanuwansu suna jujjuya su kamar wanda yake cikin magagin mutuwa yana suma. To amma da zarar tsoron ya kau, hankulansu sun dawo jikinsu sai su shiga

cutar da muminai da kausasan maganganu masu ciwo. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya siffanta su da tsananin rowar alheri idan an buƙaci hakan daga gare su. Allah ya tabbatar da cewa waɗannan mutane alal-haƙiƙa ba su yi imani ba, don haka ya lalata sakamakon ayyukansu, yin haka kuwa a wurinsa abu ne mai sauƙi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗannan munafukai ba su yi tsammanin gangamin rundunonin maƙiya za su bar Madina ba tare da sun shigo cikinta sun yi kaca-kaca da ita ba. To Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya taɓar da zatonsu ya fatattaki kafirai. Ya kuma bayyana cewa da a ce waɗannan rundunoni za su sake dawowa karo na biyu, to da sai waɗannan munafukai sun riƙa fatan su gudu su koma ƙauyuka tare da mutanen ƙauye suna tambayar labarin halin da Musulmi a Madina suke ciki, watau suna nan ko kuma kafirai sun gama da su? Sannan ya tabbatar wa muminai cewa ai in da ma za su tsaya su fita yaƙi tare da su, to ba za su taɓuka komai ba na a-zo-a-gani, don haka kada muminai su damu da su ko su yi baƙin cikin rabuwarsu da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin koyi da Annabi (ﷺ).

2. A ƙa'ida ana iya yin koyi da Annabi (ﷺ) a cikin dukkan ayyukansa sai abin da wani dalili ya keɓance.

3. Duk abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi kyakkyawa ne, babu wani abu mai muni ko kaɗan a cikinsa.

4. Wajibi ne koyinmu da Manzon Allah (ﷺ) ya zamanto mai kyau ne, babu wuce gona da iri a cikinsa babu kuma sako-sako.

5. Shar'anta yawaita zikirin Allah.

6. Kamalar gaskatawar sahabban Annabi (ﷺ) da Allah da Manzonsa lokacin da suka ga alƙawarin da Allah ya yi musu ya tabbata, sai suka bayyana yaƙininsu da harsunansu.

7. Mumini yana ƙara imani ne duk sanda ya ga wata aya ta Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

8. Ingancin mazhabar Ahlussunna masu ganin imani yana ƙaruwa ta hanyar ɗa'a ga Allah.

9. Kyakkyawan yabo ga sahabbai da tabbatar da gaskiyar imaninsu da cika alƙawarin da suka ɗaukar wa Ubangijinsu da sadaukar da rayukansu gare shi (Mai tsarki da ɗaukaka).

10. Yabo ga masu gaskiya da nuna cewa su ne suka cancanci kyakkyawan sakamako a lahira.

11. Sukan munafukai da tabbatar da cewa sun cancanci azaba a ranar alƙiyama saboda munafuncinsu.

12. Munafuki zai iya tuba Allah kuma ya karɓi tubansa. Idan kuma Allah bai nufe shi da tuba ba, to zai yi ta zama a kan munafuncinsa har ya mutu, sai Allah ya azabtar da shi a kan haka.

13. Yalwar rahamar Allah ga bayinsa masu laifi da yake ba su damar su tuba ya kuma karɓi tubansu ya yi musu gafara ya ji ƙan su.

Suratul Ahzab (21-24)

لَّقَدۡ كَانَ لَكُمۡ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٞ لِّمَن كَانَ يَرۡجُواْ ٱللَّهَ وَٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا ٢١ وَلَمَّا رَءَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلۡأَحۡزَابَ قَالُواْ هَٰذَا مَا وَعَدَنَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَصَدَقَ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥۖ وَمَا زَادَهُمۡ إِلَّآ إِيمَٰنٗا وَتَسۡلِيمٗا ٢٢ مِّنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ رِجَالٞ صَدَقُواْ مَا عَٰهَدُواْ ٱللَّهَ عَلَيۡهِۖ فَمِنۡهُم مَّن قَضَىٰ نَحۡبَهُۥ وَمِنۡهُم مَّن يَنتَظِرُۖ وَمَا بَدَّلُواْ تَبۡدِيلٗا ٢٣ لِّيَجۡزِيَ ٱللَّهُ ٱلصَّٰدِقِينَ بِصِدۡقِهِمۡ وَيُعَذِّبَ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ إِن شَآءَ أَوۡ يَتُوبَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٢٤

21. Haƙiƙa kuna da kyakkyawan abin koyi tare da Manzon Allah, ga wanda yake yin kyakkyawan fata game da Allah da ranar lahira, ya kuma ambaci Allah da yawa.

22. Lokacin kuwa da muminai suka ga rundunonin gangami sai suka ce: “Wannan shi ne abin da Allah da Manzonsa suka yi mana alƙawari, Allah kuwa da Manzonsa sun yi gaskiya. Ba kuwa abin da (wannan) ya ƙara musu sai imani da miƙa wuya.

23. Akwai wasu mazaje daga muminai da suka cika abin da suka yi wa Allah alƙawari da shi; akwai daga cikinsu wanda ya haɗu da ajalinsa, akwai kuma daga cikinsu wanda yake sauraron (ajalin); kuma ba su yi kowace irin sabawa ba (game da alƙawarin).

24. Don Allah Ya saka wa masu gaskiya a kan gaskiyarsu, Ya kuma azabtar da munafukai idan Ya ga dama, ko kuma Ya karɓi tubarsu. Lalle Allah Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa suna da kyakkyawan abin koyi a tare da Manzon Allah (ﷺ) daga maganganunsa da ayyukansa, kamar yadda yake fita da kansa wurin yaƙi, ya sadaukar da dukiyarsa da kansa domin ɗaukaka addinin Allah. To saboda me sauran Musulmi ba za su yi koyi da shi a nan ba? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa babu wanda zai yi koyi da Manzon Allah (ﷺ) sai mutumin da yake yin kyakkyawan fata game da Allah da kuma ranar lahira na samun kyakkyawan sakamako a can, yake kuma aiki domin haka, ya kuma ambaci Allah ambato mai yawa. Amma duk wanda ba haka yake ba to ba zai zama mai koyi da shi ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halayen muminai da suka bambanta da halayen munafukai, da cewa lokacin da muminai suka ga gangamin rundunar kafirai sun nufo su domin yaƙar su sai suka tabbatar da cewa wannan shi ne abin da Allah da Manzonsa suka yi musu alƙawarin faruwarsa, domin Allah da Manzonsa sun tabbatar musu da cewa sai an jarrabe su da bala’o’i iri-iri kafin nasarar Allah ta zo musu, suka nuna gaskatawarsu ga Allah da Manzonsa domin abin da suka sanar da su ga shi ya tabbata. Allah ya yi musu shaida da cewa ganinsu ga wannan rundunonin kafirai ba abin da ya ƙara musu sai imani da miƙa wuya ga Allah da umarninsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi wasu jajirtattun muminai waɗanda suka yi wa Allah alƙawari na gaskiya suka kuma cika shi, yayin da suka dage suka yi haƙuri wajen yaƙi da kafirai. Daga cikinsu akwai waɗanda suka rasu ko aka kashe su suka yi shahada; akwai kuma waɗanda suke jiran shahadar ta zo musu, ba su canza komai daga alƙawarin da suka yi wa Allah ba, kamar yadda munafukai suka canja.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Baffana wanda aka yi masa takwara da ni (watau Anas ɗan An-Nadhru) bai sami fita yaƙin Badar tare da Manzon Allah (ﷺ) ba sai abin yake damun sa ainun, har yana cewa: ‘Yanzu a ce yaƙin farko da Manzon Allah (ﷺ) ya halarta ni ban sami halartar sa ba. Idan har Allah ya nuna mini lokacin da zan halarci wani yaƙi tare da Manzon Allah (ﷺ) to Allah zai ga abin da zan aikata.’ Sai ya ji nauyin ya yi wata maganar ban da wannan. Sai ya sami halartar yaƙin Uhudu tare da Manzon Allah (ﷺ). Sai Sa’adu ɗan Mu’azu ya haɗu da shi sai Anas ya tambaye shi ya ce: ‘Ya Baban Amru

ina zuwa ne?’ Sannan ya ce: ‘Wayyo ina jiyo ƙanshin Aljanna kafin in ƙarasa dutsen Uhudu!’ Nan take ya shiga yaƙar kafirai har sai da aka kashe shi, aka sami gurbin suka da sara da harbi har tamanin da ɗoriya a jikinsa. Sai ‘yar’uwarsa Rubayyi’u ‘yar Nadhru (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: ‘Ban gane gawar ɗan’uwana ba sai ta hanyar zanen ‘yan yatsunsa.’ Sai wannan ayar ta 23 ta sauka. Sahabbai suna ganin a kansa ne da sauran abokansa wannan ayar ta sauka.” [Muslim #1903].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin da ya sanya yake jarrabar muminai a nan duniya, watau domin ya saka wa masu gaskiya waɗanda suka cika wa Allah alƙawarin da suka ɗaukar masa. Su kuma munafukai ya azabtar da su saboda karya alƙawarinsu; idan ya ga damar yi musu haka sai ya karɓi ransu tun gabanin su tuba su bar kafirci. Idan kuma ya ga dama sai ya datar da su su tuba su koma gare shi, domin shi ya tabbata mai gafara ne ga wanda ya tuba mai rahama ne gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafiran da suka yi wa Manzon Allah da sahabbansa gangami domin su yaƙe su, mutane ne da zukatansu suke cike da jin haushin Musulmi da Musulunci.

2. Allah shi kaɗai ya isa ya ba wa muminai kariya daga makiyansu komai yawansu da ƙarfinsu.

3. Yahudawa al’umma ce mai cin amana da yaudara.

4. Idan Musulmi suka ci ƙasa da yaƙi to ta zama mallakinsu.

5. Halaccin cin ganimar yaƙi ga wannan al’umma, saɓanin al’ummun annabawan da suka gabata, su ba a halatta musu su ci ganimar yaƙi ba.

Suratul Ahzab (25-27)
وَرَدَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِغَيۡظِهِمۡ لَمۡ يَنَالُواْ خَيۡرٗاۚ وَكَفَى ٱللَّهُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٱلۡقِتَالَۚ وَكَانَ ٱللَّهُ قَوِيًّا عَزِيزٗا ٢٥ وَأَنزَلَ ٱلَّذِينَ ظَٰهَرُوهُم مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ مِن صَيَاصِيهِمۡ وَقَذَفَ فِي قُلُوبِهِمُ ٱلرُّعۡبَ فَرِيقٗا تَقۡتُلُونَ وَتَأۡسِرُونَ فَرِيقٗا ٢٦ وَأَوۡرَثَكُمۡ أَرۡضَهُمۡ وَدِيَٰرَهُمۡ وَأَمۡوَٰلَهُمۡ وَأَرۡضٗا لَّمۡ تَطَـُٔوهَاۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٗا ٢٧

25. Allah kuma Ya komar da waɗanda suka kafirta da fushinsu ba su sami wani alheri ba. Allah kuma Ya ɗauke wa muminai yin yaƙi. Domin kuwa Allah Ya kasance Mai ƙarfi ne, Mabuwayi.

26. Ya kuma sauko da waɗanda suka taimake su daga ma’abota littafi daga ganuwoyinsu Ya kuma jefa tsoro a zukatansu, wasu jama’ar kuke kashe su kuna kuma ribace wasu jama’ar.

27. Ya kuma gadar muku ƙasarsu da gidajensu da dukiyoyinsu, da kuma wata ƙasa ma da ba ku taɓa taka ta ba. Allah kuwa Ya kasance Mai iko ne a kan komai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya murƙushe gangamin rundunonin kafiran Kuraishawa da ƙabilar Gaɗafanu da waɗanda suke tare da su ya sanya su cikin baƙin ciki da damuwar rashin cim ma burinsu na cin muminai da yaƙi. Allah kuma ya ɗauke wa muminai wannan yaƙin ya aiko wa da kafirai wata guguwa mai ƙarfi ya kuma saukar da mala’iku ya fatattaki rundunar kafirai da su. Allah ya tabbatar da cewa shi mai ƙarfi ne mabuwayi, babu mai iya ja da shi ko ya yi nasara a kansa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance idan yana dawowa daga wurin yaƙi ko hajji ko umara yakan fara yin kabarbari uku sannan ya ce: “Babu abin bauta da gaskiya sai Allah ba shi da abokin tarayya, mulki da yabo nasa ne, shi kuma mai iko ne a kan komai. Mu masu dawowa ne, masu tuba ne, masu bauta ne, masu sujjada ne ga Ubangijinmu, masu godiya ne. Allah ya gaskata alƙawarinsa ya taimaki bawansa ya karya rundunoni shi kaɗai.” [Bukhari #4116 da Muslim #1344].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abu Aufa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya yi mummunar addu’a ga rundunonin kafirci ya ce: “Ya Allah, ya wanda ya saukar da littafi, mai gaggawar hisabi, ka karya gangamin rundunonin kafirai. Ya Allah, ka karya su, ka girgiza su.” [Bukhari #2933 da Muslim #1744].

An karɓo daga Sulaimanu ɗan Surad (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: A ranar yaƙin Gwalalo Annabi (ﷺ) ya ce: “Nan gaba mu ne za mu fita yaƙar su ba su ne za su fito yaƙar mu ba.” [Bukhari #4109]. Watau bayan an fatattake su a wannan yaƙin.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya azabtar da Yahudawan da suka mara wa kafirai baya, watau Yahudawan Banu Kuraiza, da cewa ya sauko da su daga ganuwoyinsu waɗanda suka tanada domin kare kawunansu daga maƙiyansu. Allah kuma ya jefa tsoro a zukatansu suka kasa yin fito-na-fito da Musulmi suka miƙa wuya a gare su cikin wulaƙanci, Allah ya ɗora muminai a kansu suka riƙa kashe mazajensu waɗanda za su iya yin yaƙi suka kuma ribace mata da ƙananan yara.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan ya hallaka Yahudawa ya mallaka wa Musulmi gonakinsu na dabino da shuke-shuke, ya kuma mallaka musu gidajensu da sauran dukiyoyinsu, sai kuma ya yi wa Musulmi albishir da cewa ya mallaka musu wata ƙasa da ba su taɓa taka ta da ƙafafunsu ba, ita ce ƙasar Khaibar wadda Musulmi suka same ta bayan shekara bakwai da hijirar Annabi (ﷺ), bayan kuma shekara biyu da gama yaƙin Gwalalo. Tabbas Allah kuwa mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gagarar sa.

An karɓo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Yayin da Manzon Allah (ﷺ) ya dawo daga yaƙin Gwalalo, ya ajiye makamansa ya yi wanka sai Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo masa ya ce: “Shin ka ajiye makamanka ne? Mu dai mala’iku wallahi har zuwa yanzu ba mu ajiye namu ba. Don haka ka fita zuwa gare su.” Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Zuwa ina?” Ya ce: “Nan nan kusa.” Sai ya nuna ɓangaren Yahudawan Banu Kuraiza. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya fita zuwa gare su. [Bukhari #2413 da Muslim #1769].

Annabi (ﷺ) ya yi musu ƙawanya har tsawon kwana ashirin da biyar, shugaban Yahudawa Ka’abu ɗan Asad ya yi wa jama'arsa Yahudawa tayin su zaɓi ɗaya daga cikin abubuwa uku:

1. Ko dai su musulunta;

2. Ko kuma su kashe ‘ya’yansu da matansu da hannuwansu sannan su zare takubbansu su fita su yaƙi Musulmi ko su yi nasara ko a kashe su;

3. Ko kuma su bari sai ranar Assabar su shammaci Musulmi su auka musu, domin ba za su yi zaton za su yaƙe su a ranar Assabar ba.
Amma ‘yan’uwansu Yahudawa suka shure duk waɗannan abubuwan uku.
Sai daga ƙarshe suka yarda da duk wani hukuncin da Sa’ad ɗan Mu’azu zai yanke a kansu, domin suna ganin sun ƙulla ƙawance da shi a zamanin jahiliyya. Sai Annabi (ﷺ) ya sa aka je aka zo da shi a kan jaki ba shi da lafiya, sai shi kuma ya yanke hukuncin cewa a kashe duk mazajensu waɗanda za su iya yaƙi, a kama ‘ya’yansu da matansu a matsayin ribar yaƙi. [Dubi, Bukhari #4121 da Muslim #1768].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Raba Manzon Allah (ﷺ) da duk wata mata da take fifita ƙaunar duniya a kan ƙaunar Allah da Manzonsa da gidan lahira.

2. Girman martabar matan Manzon Allah (ﷺ) da yadda suka sanya ƙaunar Allah da Manzonsa da gidan lahira ita ce babban muradinsu, ba ƙyale-ƙyalen duniya ba.

3. Dacewar Manzon Allah (ﷺ) da matan aure nagari. Watau kamar yadda yake mafi kamala cikin halittun Allah, to hakanan Allah ya datar da shi ga samun mata masu kamala nagartattu.

4. Miji ya ba wa matarsa zaɓin zama tare da shi ko kuma saki, ba ya zama saki.

5. Girman ladan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanada ga matan Annabi (ﷺ).

6. Cikar adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka); yayin da ya yi alƙawarin ninka azaba ga matar Annabi (ﷺ) idan ta saɓa masa, kamar yadda ya yi alƙawarin ninka mata ladanta idan ta yi masa biyayya.

Suratul Ahzab (28-31)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ قُل لِّأَزۡوَٰجِكَ إِن كُنتُنَّ تُرِدۡنَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا وَزِينَتَهَا فَتَعَالَيۡنَ أُمَتِّعۡكُنَّ وَأُسَرِّحۡكُنَّ سَرَاحٗا جَمِيلٗا ٢٨ وَإِن كُنتُنَّ تُرِدۡنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَٱلدَّارَ ٱلۡأٓخِرَةَ فَإِنَّ ٱللَّهَ أَعَدَّ لِلۡمُحۡسِنَٰتِ مِنكُنَّ أَجۡرًا عَظِيمٗا ٢٩ يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِيِّ مَن يَأۡتِ مِنكُنَّ بِفَٰحِشَةٖ مُّبَيِّنَةٖ يُضَٰعَفۡ لَهَا ٱلۡعَذَابُ ضِعۡفَيۡنِۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٗا ٣٠ ۞وَمَن يَقۡنُتۡ مِنكُنَّ لِلَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتَعۡمَلۡ صَٰلِحٗا نُّؤۡتِهَآ أَجۡرَهَا مَرَّتَيۡنِ وَأَعۡتَدۡنَا لَهَا رِزۡقٗا كَرِيمٗا ٣١

28. Ya kai wannan Annabi, ka gaya wa matanka: “Idan kun kasance kuna son rayuwar duniya ne da kuma adonta, to sai ku zo in jiyar da ku daɗi, in kuma sake ku kyakkyawan saki.

29. “Idan kuwa kun kasance kuna ƙaunar Allah ne da Manzonsa da kuma ranar lahira, to haƙiƙa Allah Ya tanadi lada mai girma ga masu kyautatawa daga cikinku.

30. Ya ku matan Annabi, duk wadda ta zo da wani abin ƙi na sarari daga cikinku to za a ninninka mata azaba ninki biyu. Yin wannan kuma ya kasance abu ne mai sauƙi ga Allah.

31. Duk kuwa wadda ta yi biyayya ga Allah da Manzonsa daga cikinku ta kuma yi aiki nagari, to za Mu ba ta ladanta sau biyu, kuma Mun tanadar mata arziki mai girma.

Waɗannan ayoyi sun sauka ne lokacin da matan Annabi (ﷺ) suka haɗa baki suka same shi, suna neman sa da ya ƙara musu a kan abin da yake yi musu na ciyarwa da tufatarwa, suka nemi abin da ya fi ƙarfinsa. To sai abin ya dame shi sosai har ta kai ya yi rantsuwar ba zai sake shiga ɗakin kowa ce daga cikinsu ba har tsawon wata guda. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi nufin kawo masa sauƙi cikin lamarin ya kuma yi nufin ɗaukaka darajar matansa, ya tsarkake su daga duk wani abu da zai zubar musu mutuncinsu. Sai ya umarce shi da ya ba su zaɓin cewa, idan sun kasance rayuwar duniya suke so da kuma ƙyale-ƙyalen da ke cikinta, to su zo ya ba su ɗan abin more rayuwa da ake ba wa matan da aka saki, sannan sai ya sake su kyakkyawan saki wanda babu cutarwa a cikinsa. Idan kuwa sun kasance suna neman yardar Allah da Manzonsa ne, suna ƙaunar gidan Aljanna a lahira, to su yi haƙuri da rayuwar da suke ciki kuma lalle Allah

ya tanadi lada mai girma ga duk wadda ta kyautata zamantakewarta da Manzon Allah ta yi haƙuri da rayuwar da take ciki.

An karƀo daga A'isha matar Manzon Allah (ﷺ) ta ce: "Yayin da aka umarci Manzon Allah (ﷺ) cewa ya ba wa matansa zaɓi sai ya fara da ni ya ce mini: 'Lalle zan faɗa miki wani al'amari, to amma kada ki yi gaggawa har sai kin nemi shawarar mahaifanki.' Ta ce: "Annabi (ﷺ) ya riga ya san mahaifana ba za su taɓa ba ni shawarar rabuwa da shi ba. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya karanta waɗannan ayoyi na 28-29". Sai A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: "A kan wanne abu ne a nan da har sai na yi shawara da mahaifana, lalle ni ina ƙaunar Allah da Manzonsa da gidan lahira." Ta ce: "Sauran matayen Manzon Allah (ﷺ) su ma suka yi irin yadda na yi." [Bukhari #4786 da Muslim #1475].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara jan kunnensu da yi musu albishir idan sun kyautata ayyukansu, ya kira su da 'matan Annabi' domin su fahimci girman matsayinsu, ya tabbatar musu da cewa duk wadda ta zo da wani saɓon Allah a sarari, to za a ninka mata azabarta ninki biyu a ranar alƙiyama saboda matsayinta da ba da kariya ga mutuncin Manzon Allah. Allah kuma ya nuna wannan riɓanya azabar a wurinsa abu ne mai sauƙi.
Sannan ya nuna musu cewa wadda kuma ta ɗore a kan biyar Allah da Manzonsa, ta kuma yi aiki nagari, to ita ma Allah zai ninka mata ladanta har sau biyu, kuma a lahira Allah ya tanadar mata wani lada na karamci, watau gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman martabar matan Annabi (ﷺ) da fifikonsu a kan sauran matan wannan al'umma.

2. Haramun ne ga mace ta riƙa tausasa muryarta yayin da take magana da mazajen da ba muharramanta ba, domin yin haka yakan iya jawo faruwar wata fitina.

3. Muryar mace ba al'aura ce ba, don haka aka yi mata izini ta yi maganar da ta dace, watau ko da ga wasu mazaje ne da ba muharramanta ba idan har buƙatar hakan ta taso.

4. Fitinar sha'awar mata wata cuta ce a zuciya da take buƙatar a magance ta.

5. Asali ga mace shi ne zamanta a cikin gidanta. Ya halatta ta fita yayin da buƙatar fitar ta taso, amma ba tare da bayyana adonta ba.

6. Haramcin mace ta riƙa nuna adonta ga wasu mazaje waɗanda ba muharramanta ba, domin wannan aiki ne na mata a zamanin jahiliyya. Amma babu laifi ta bayyana adonta yayin da take cikin gidanta ko a cikin mata 'yan'uwanta.

7. Falalar iyalan gidan Manzon Allah (ﷺ), matansa kuma suna cikin iyalan gidansa.

8. Wanke matan Annabi (ﷺ) daga zunubai da aikata abin da zai jawo musu fushin Allah da Manzonsa (ﷺ).

9. Wanda Allah ya ba shi ilimin sanin addini, to akan buƙaci riƙo da addini a wurinsa fiye da wanda ba shi da ilimi.

10. Gidan da ake karanta littafin Allah a cikinsa ya fi alheri a kan wanda ba a karanta shi a cikinsa.

11. Sunnar Annabi (ﷺ) ita ma wahayi ce kamar Alƙur’ani, dole ne a yi riƙo da ita.

Suratul Ahzab (32-34)

يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِيِّ لَسۡتُنَّ كَأَحَدٖ مِّنَ ٱلنِّسَآءِ إِنِ ٱتَّقَيۡتُنَّۚ فَلَا تَخۡضَعۡنَ بِٱلۡقَوۡلِ فَيَطۡمَعَ ٱلَّذِي فِي قَلۡبِهِۦ مَرَضٞ وَقُلۡنَ قَوۡلٗا مَّعۡرُوفٗا ٣٢ وَقَرۡنَ فِي بُيُوتِكُنَّ وَلَا تَبَرَّجۡنَ تَبَرُّجَ ٱلۡجَٰهِلِيَّةِ ٱلۡأُولَىٰۖ وَأَقِمۡنَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتِينَ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِعۡنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓۚ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُذۡهِبَ عَنكُمُ ٱلرِّجۡسَ أَهۡلَ ٱلۡبَيۡتِ وَيُطَهِّرَكُمۡ تَطۡهِيرٗا ٣٣ وَٱذۡكُرۡنَ مَا يُتۡلَىٰ فِي بُيُوتِكُنَّ مِنۡ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ وَٱلۡحِكۡمَةِۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ لَطِيفًا خَبِيرًا ٣٤

32. Ya ku matan Annabi, ku fa ba kamar sauran mata kuke ba. Idan kun kiyaye dokokin Allah, to kada ku tausasa murya har yadda wani mai raunin imani a zuciyarsa zai yi kwaɗayin (wani abu), kuma ku yi Magana irin maganar da ta dace da shari’a.

33. Ku kuma zauna a cikin gidajenku, kada kuma ku riƙa fita (da bayyana ado) irin ta jahiliyyar farko; ku kuma tsayar da salla, ku ba da zakka, ku kuma bi Allah da Manzonsa. Abin da Allah Yake nufi kawai shi ne Ya kawar muku da duk wata ƙazanta, ya ku iyalin gidan Annabi, Ya kuma tsarkake ku tsarkakewa.

34. Kuma ku tuna abin da ake karantawa a cikin gidajenku na ayoyin Allah da kuma hikima. Lalle Allah Ya kasance Mai tausayawa ne, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa matan Annabi (ﷺ) cewa su sani su fa ba kamar sauran mata suke ba wajen daraja da ɗaukaka da matsayi; su Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fifita darajarsu a kan ta sauran mata matuƙar za su kiyaye dokokin Allah su ji tsoron sa.
Sai kuma Allah ya hana su tausasa murya idan suna magana da mazajen da ba muharramansu ba, domin yin haka zai sanya wanda yake da wata cuta ta munafurci ko sha’awa ta haram ya yi kwaɗayin wani abu tare da su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya umarce su da su yi maganar da ta dace da gwargwadon buƙata wadda ba za ta ja hankali ba.
Sannan kuma ya umarce su da su zauna a cikin gidajensu kada su riƙa fita yawo sai da buƙata, kada kuma su riƙa bayyana adonsu irin yadda mata suke yi a zamanin jahiliyya kafin zuwan Musulunci, yadda suke fito da kwalliyarsu don su ja hankulan mazaje.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kada ku hana bayin Allah mata fita zuwa masallatan Allah, su kuma su fita ba cikin kwalliya ba.” [Abu Dawud #565].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Mace al’aura ce, idan ta fita daga gidanta sai Shaiɗan ya sanya idanunsa a kanta, lokacin da ta fi kusanci da Ubangijinta shi ne lokacin da take zaune ƙuryar gidanta.” [Ṭabarani, *Al-Mu’ujamul Ausaɗ* #2890].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da tsayar da salla yadda ya dace, su kuma fitar da zakkar dukiyoyinsu, kuma su bi Allah da Manzonsa, ya nuna musu cewa ya umarce su da waɗannan abubuwa ne ba don komai ba sai don yana nufin gusar musu da duk wata ƙazanta ya tsarkake musu zukatansu, ya yi musu kwalliya da kyawawan ɗabi’u ya raba su da munana domin su Ahalin gidan Annabi ne (ﷺ).

Haka kuma ya umarce su da su riƙa tuna ayoyin Allah da aka saukar wa Manzon Allah (ﷺ) waɗanda ake karanta su a gidajensu da kuma sunnar Manzo (ﷺ) wadda suke samu daga wurinsa, ya tabbatar musu cewa shi mai tausasawa ne gare su yayin da ya yi musu tagomashin kasancewa matan Manzonsa (ﷺ), kuma masani ne mai cikakken sani a lokacin da ya zaɓe su a matsayin matan Manzonsa (ﷺ), ya kuma mayar da su iyayen muminai.

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda), ta ce: Wata rana Annabi (ﷺ) ya fito da safe sanye da wani mayafi mai zanen sirdin raƙuma a jikinsa, sai Hasan ɗan Aliyyu ya zo sai Manzon Allah (ﷺ) ya shigar da shi cikinsa, sai kuma Husaini shi ma ya zo, sai Manzo (ﷺ) ya shigar da shi cikin wannan mayafi, sai Faɗima ta zo ita ma ya shigar da ita ciki, sannan sai Aliyyu ya zo shi ma Manzon Allah (ﷺ) ya shigar da shi ciki, sannan sai ya ce: "Abin da Allah yake nufi kawai shi ne ya kawar muku da duk wata ƙazanta, ya ku Ahalin gidan Annabi, ya kuma tsarkake ku tsarkakewa." [Muslim #2424].

An karɓo daga Umar ɗan Abu Salama (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da wannan aya ta sauka ga Annabi (ﷺ) yana gidan Ummu Salama (Allah ya ƙara mata yarda), sai ya kirawo Faɗima da Hasan da Husaini sai ya lulluɓe su a cikin mayafi, Aliyyu kuma yana bayansa shi ma ya lulluɓe shi, sannan ya ce: "Ya Allah, waɗannan Ahalin gidana ne, ka gusar musu da ƙazanta, ka kuma tsarkake su tsarkakewa sosai." Ummu Salama ta ce: "Ni ma ina tare da su ya Annabin Allah?" Sai ya ce: "Ke kina nan a kan matsayinki, kina kuma tattare da alheri." [Tirmizi #3205].

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daidaito tsakanin jinsin maza da na mata a wajen imani da Allah da wajabcin bin dokokinsa da cancantar samun kyakkyawan sakamako a lahira ga wanda ya kyautata aikinsa a duniya daga cikinsu.

2. Musulunci ba shi ne imani ba, sai dai duk mumini Musulmi ne.

3. Falalar siffantuwa da waɗannan kyawawan siffofi da aka ambata a ayar.

4. Fifikon jinsin maza a kan na mata a Musulunci, don haka aka gabatar da su a duk wannan ayar. Don haka ya dace a fara ambaton maza kafin mata a cikin duk wani al'amari da ya jiɓinci jinsunan biyu, saɓanin yadda lamarin yake a wurin waɗanda ba Musulmi ba da wasu masu kwaikwayon su ido-rufe wajen gabatar da jinsin mata a kan na maza idan suna magana da jinsunan biyu.

5. Sakamakon da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ba wa waɗanda suka yi ayyuka nagari ya ninninka ayyukan nasu.

Suratul Ahzab (35)

إِنَّ ٱلْمُسْلِمِينَ وَٱلْمُسْلِمَٰتِ وَٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ وَٱلْقَٰنِتِينَ وَٱلْقَٰنِتَٰتِ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلصَّٰدِقَٰتِ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰبِرَٰتِ وَٱلْخَٰشِعِينَ وَٱلْخَٰشِعَٰتِ وَٱلْمُتَصَدِّقِينَ وَٱلْمُتَصَدِّقَٰتِ وَٱلصَّٰٓئِمِينَ وَٱلصَّٰٓئِمَٰتِ وَٱلْحَٰفِظِينَ فُرُوجَهُمْ وَٱلْحَٰفِظَٰتِ وَٱلذَّٰكِرِينَ ٱللَّهَ كَثِيرًا وَٱلذَّٰكِرَٰتِ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا ﴿٣٥﴾

35. Lalle Musulmi maza da Musulmi mata, da muminai maza da muminai mata, da masu biyayya maza da masu biyayya mata, da masu gaskiya maza da masu gaskiya mata, da masu haƙuri maza da masu haƙuri mata, da masu ƙaskantar da kai maza da masu ƙaskantar da kai mata, da masu sadaka maza da masu sadaka mata, da masu azumi maza da masu azumi mata, da maza masu kiyaye farjinsu da mata masu kiyaye farjinsu, da maza masu ambaton Allah da yawa da mata masu ambaton Allah (da yawa, dukkaninsu) Allah ya tanadar musu gafara da lada mai girma.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da daidaiton jinsin maza da na mata dangane da

bautar Allah da imani da shi da kuma aikata kyawawan ayyuka da cancantar samun kyakkyawan sakamako a lahira.
Allah ya siffanta maza da mata da kyawawan siffofi goma, su ne:
Na farko, Musulunci, watau miƙa wuya ga Allah ta hanyar aikata abin da ya yi umarni da shi da barin abin da ya hana.
Na biyu, imani, wanda yake nufin ƙudurce duk wani abu da Allah ya nemi Musulmi ya gaskata shi.
Na uku, dawwama a kan biyayyar Allah cikin natsuwa.
Na huɗu, gaskiya a cikin maganganu da ayyuka.
Na biyar, haƙuri a kan ɗa'a ga Allah da guje wa abin da ya hana, da haƙuri a kan abin da Allah zai ƙaddara wa bawa marar daɗi.
Na shida, ƙaskantar da kai da tawalu'u ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Na bakwai, sadaka da dukiya da taimaka wa mabuƙata.
Na takwas, azumi wanda ya ƙunshi na farilla da na nafila.
Na tara, kiyaye mutunci daga aukawa cikin laifin zina da abubuwan da suke jawowa a faɗa cikinta.
Na goma, ambaton Allah da yawa da harsuna da zukata.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk waɗanda suka haɗa waɗannan siffofi to ya yi musu tanadin gafara da lada mai girma, watau gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin yarda da miƙa wuya ga hukuncin Allah da Manzonsa (ﷺ).

2. Yana daga cikin abin da imani yake haifar wa bawa, miƙa wuya da rashin saɓa wa hukuncin Allah da na Manzonsa (ﷺ). Duk sanda imanin bawa ya yi ƙarfi to biyayya ga Allah da Manzonsa (ﷺ) sai ta ƙara haɓaka. Idan kuwa imanin ya yi rauni sai ita ma biyayyar ta yi rauni.

3. Duk hukuncin da Manzon Allah (ﷺ) ya yi to daidai yake da hukuncin Allah, saɓa masa kuma saɓa wa Allah ne.

4. Ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Zaidu ɗan Harisa ta Musulunci da riƙo da shi.

5. Samun 'yanci daga bauta ni'ima ce babba, haka ma ga wanda ya 'yanta bawan, ya yi masa sanadiyyar samun ta.

6. Miji shi ne yake riƙe da matarsa, don haka duk ɗawainiyarta tana kansa, ita kuma tana ƙarƙashin kulawarsa ne.

7. Neman shawarar mutane nagari a kan al'amura masu muhimmanci, kamar yadda Zaidu ya riƙa neman shawarar Annabi (ﷺ) game da matsalarsa da matarsa. Wajibi ne kuma a kan wanda aka nemi shawara a wurinsa ya ba da kyakkyawar shawara.

8. Yana da kyau ga mijin da ya sami matsala da matarsa kada ya yi gaggawar sakin ta, ya yi ƙoƙarin riƙe ta sai dai idan abu ya ta'azzara.

9. Tabbatar da gaskiyar manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ). Da a ce Manzon Allah maƙaryaci ne to da ya ɓoye wannan al'amari na auren Zainab domin girmansa a wurinsa.

10. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya zaɓa wa Manzonsa (ﷺ) saɓanin abin da shi Manzo (ﷺ) ya fi so, don wata hikima tasa.

11. Wajabcin gabatar da tsoron Allah a kan tsoron mutane.

12. Falalar Zainab ‘yar Jahshi, domin ita Allah ne da kansa ya ɗaura aurenta ba iyayenta ba.

13. Duk hukuncin da ya shafi Manzon Allah (ﷺ) to ya shafi al’ummarsa sai abin da wani dalili ya togace.

14. Annabi (ﷺ) shi kansa bawan Allah ne, ba ya halatta a gare shi ya fice daga bin shari’ar Allah.

15. Zartar da hukunci a aikace ya fi tasiri a kan faɗar sa da baki.

16. Dukkan annabawan Allah sun isar da saƙon Allah zuwa ga al’ummunsu, kuma ba su ji tsoron wani ba sai Allah. Wannan ya tabbatar da cewa babu abin da suka ɓoye wa al’ummunsu.

17. Annabi Muhammadu (ﷺ) bai bar wani ɗa namiji ba, duk ‘ya’yansa maza mutuwa suke yi tun suna ƙanana. ‘Yarsa ɗaya ce ta rayu bayansa, ita ce Faɗima (Allah ya ƙara masa yarda), ita ma ta rasu bayan wafatinsa da wata shida rak.

18. Annabi Muhammadu (ﷺ) shi ne cikamakin annabawa da manzanni. Babu wani annabi da Allah ya aiko a bayansa. Duk waɗanda suka yi da’awar annabci a bayansa ko za su yi nan gaba, to maƙaryata ne zindiƙai, kamar irin su Al-Aswad Al-Ansi da Musailima da Mirza Gulam Ahmad annabin ƙarya na mabiya addinin Ƙadyaniyya ko Ahmadiyya.

Suratul Ahzab (36-40)

وَمَا كَانَ لِمُؤۡمِنٖ وَلَا مُؤۡمِنَةٍ إِذَا قَضَى ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ أَمۡرًا أَن يَكُونَ لَهُمُ ٱلۡخِيَرَةُ مِنۡ أَمۡرِهِمۡۗ وَمَن يَعۡصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلٗا
مُّبِينٗا ٣٦ وَإِذۡ تَقُولُ لِلَّذِيٓ أَنۡعَمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ وَأَنۡعَمۡتَ عَلَيۡهِ أَمۡسِكۡ عَلَيۡكَ زَوۡجَكَ وَٱتَّقِ ٱللَّهَ وَتُخۡفِي فِي نَفۡسِكَ مَا ٱللَّهُ مُبۡدِيهِ وَتَخۡشَى ٱلنَّاسَ
وَٱللَّهُ أَحَقُّ أَن تَخۡشَىٰهُۖ فَلَمَّا قَضَىٰ زَيۡدٞ مِّنۡهَا وَطَرٗا زَوَّجۡنَٰكَهَا لِكَيۡ لَا يَكُونَ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ حَرَجٞ فِيٓ أَزۡوَٰجِ أَدۡعِيَآئِهِمۡ إِذَا قَضَوۡاْ مِنۡهُنَّ وَطَرٗاۚ
وَكَانَ أَمۡرُ ٱللَّهِ مَفۡعُولٗا ٣٧ مَّا كَانَ عَلَى ٱلنَّبِيِّ مِنۡ حَرَجٖ فِيمَا فَرَضَ ٱللَّهُ لَهُۥۖ سُنَّةَ ٱللَّهِ فِي ٱلَّذِينَ خَلَوۡاْ مِن قَبۡلُۚ وَكَانَ أَمۡرُ ٱللَّهِ قَدَرٗا مَّقۡدُورًا ٣٨
ٱلَّذِينَ يُبَلِّغُونَ رِسَٰلَٰتِ ٱللَّهِ وَيَخۡشَوۡنَهُۥ وَلَا يَخۡشَوۡنَ أَحَدًا إِلَّا ٱللَّهَۗ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ حَسِيبٗا ٣٩ مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٖ مِّن رِّجَالِكُمۡ وَلَٰكِن
رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَۗ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٗا ٤٠

36. Bai kamata ga wani mumini ko wata mumina ba, idan Allah da Manzonsa suka yi hukunci a kan wani al’amari su zama suna da wani zaɓi game da al’amarinsu. Wanda kuwa ya saba wa Allah da Manzonsa, to haƙiƙa ya ɓata, bayyanannen ɓata.

37. (Ka tuna) lokacin da kake ce wa wannan da Allah Ya yi wa ni’ima, kai ma ka yi masa ni’ima: “Riƙe matarka, kuma ka kiyaye dokokin Allah”, alhali kuwa kana ɓoyewa a cikin ranka abin da Allah zai bayyana shi, kana kuma tsoron mutane, alhali kuma Allah ne Ya fi cancanta ka ji tsoron Sa; to lokacin da Zaidu ya gama buƙatarsa da ita (matarsa Zainab), Mun aurar maka ita, don saboda kada ya zama akwai ƙuntatawa ga muminai game da (auren) matan ‘ya’yansu na riƙo lokacin da suka gama bukata da su. Al’amarin Allah kuwa ya kasance abin zartarwa ne.

38. Babu wani laifi a kan Annabi game da abin da Allah Ya halatta masa; (wannan kuwa) Sunnar Allah ce ga waɗanda suka gabace ka (daga annabawa). Al'amarin Allah kuwa ya kasance mai tabbata ne ba makawa.

39. Waɗanda suke isar da saƙon Allah suke kuma tsoron Sa, ba sa kuwa tsoron kowa sai Allah. Allah kuwa Ya isa Mai yin hisabi.

40. (Annabi) Muhammadu bai kasance uban ɗaya daga cikin mazajenku ba, sai dai (shi) ya kasance Manzon Allah ne kuma cikamakin annabawa. Allah kuma Ya kasance Masanin komai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ba ya dacewa ga mumini namiji ko mace idan Allah da Manzonsa (ﷺ) sun yanke wani hukunci ya zamanto suna da wani zaɓi nasu na kansu; a kan su karɓi wannan hukunci ko su yi watsi da shi. Dole ne su yarda da abin da Allah da Manzonsa suka zartar ko da kuwa ya saba wa son zuciyarsu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana hukuncin wanda ya saba masa ko ya saba wa Manzonsa (ﷺ) da cewa ya ɓata ɓata mabayyani, domin ya saki hanyar da za ta kai shi ga samun yardar Allah, ya kama hanyar faɗawa cikin azabar wutar Jahannama.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci ƙissar Zaidu ɗan Harisa (Allah ya ƙara masa yarda) da umarnin da ya yi wa Manzonsa (ﷺ) na auren matar Zaidu (Allah ya ƙara masa yarda) bayan ya sake ta.
Dalilin saukar waɗannan ayoyi shi ne, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi nufin rushe wata al'ada ta jahiliyya ne dangane da 'ya'yan riƙo waɗanda ba daidai suke da 'ya'yan cikin mutum ba. Gabanin wannan hukunci da Allah ya zartar, Larabawa sun yarda da cewa idan mutum yana riƙon wani a matsayin ɗansa, to haramun ne a kansa ya auri matar da ya saki, domin a wurinsu kamar ya auri matar ɗan da ya haifa ne bayan ya sake ta.
Annabi (ﷺ) ya riƙi Zaidu ɗan Harisa (Allah ya ƙara masa yarda) kamar ɗansa, har ma ana kiran sa Zaidu ɗan Muhammad, sai bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana a danganta kowa in ba ga mahaifinsa ba, shi ne aka dawo ana kiran sa da Zaidu ɗan Harisa (Allah ya ƙara masa yarda).
Annabi (ﷺ) yana matuƙar ƙaunar Zaidu (Allah ya ƙara masa yarda), har ma ana kiran sa da ɗan lelen Manzon Allah. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya aura masa Zainab 'yar Jahshi wadda ita kuma 'yar gwaggon Manzon Allah ce Umaimatu 'yar Abdulmuɗɗalib. Ya zauna da ita tsawon shekara guda, daga baya zamansu ya fara samun matsala, shi kuma Zaidu (Allah ya ƙara masa yarda) ya riƙa kawo ƙarar ta wajen Manzon Allah (ﷺ), shi kuma yana lallashin sa yana faɗa masa ya ji tsoron Allah ya riƙe matarsa.
To da yake Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi nufin rushe waccan al'ada ta jahiliyya sai ya sanar da Manzonsa cewa Zaidu (Allah ya ƙara masa yarda) zai saki matarsa Zainab shi kuma zai aure ta bisa umarnin Allah. Wannan lamari ya yi wa Manzon Allah (ﷺ) girma a ransa ainun, domin tsoron abin da mutane za su riƙa faɗa na cewa ya auri matar ɗansa na riƙo. Don haka sai ya ɓoye wannan al'amari a zuciyarsa bai faɗa wa kowa ba, Allah kuwa ya nuna masa bai dace gare shi ya ji tsoron mutane ba, shi kaɗai ya kamata ya ji tsoro.

Da zama ya ƙi yiwuwa tsakanin Zaidu da matarsa Zainab sai ya sake ta, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ya aurar da ita ga Manzonsa (ﷺ). Daga wannan lokaci kuma Allah Ya rushe waccan al'adar ta jahiliyya, ya saukar da waɗannan ayoyi yana umartar Annabi (ﷺ) ya tuna sanda yake umartar Zaidu wanda Allah ya yi masa ni'imar Musulunci da imani da biyayya ga Manzonsa (ﷺ), shi kuma ya yi masa ni'imar 'yanta shi daga bauta, Annabi kuma yake umartar sa da ya riƙe matarsa Zainab, ya ji tsoron Allah ta hanyar bin umarninsa da barin abin da ya hana shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zargi Annabi da cewa yana ɓoye wani abu a ransa, watau wahayin da Allah ya yi masa na auren Zainab da zai yi don jin tsoron mutane. Allah kuwa sai ya bayyana wannan lamari, don haka Allah ya kamata Annabi ya ji tsoro ba mutane ba. Yayin da zaman auren Zaidu da Zainab ya zo ƙarshe sai Allah ya aura masa ita, domin ya tabbatar babu wani laifi ga muminai

su auri matan ‘ya’yansu na riƙo bayan sun sake su sun kammala iddarsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya daɗa tabbatar da cewa al’amarinsa abin zartarwa ne babu wanda ya isa ya hana faruwarsa.

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Lokacin da iddar Zainab ta ƙare, Annabi (ﷺ) ya ce wa Zaidu: ‘Ka je ka yi mata maganata.’ Sai Zaidu (Allah ya ƙara masa yarda) ya tafi ya same ta tana kwaɓin garinta, Zaidu ya ce: “Yayin da na gan ta sai ta yi mini kwarjini har na kasa ci gaba da kallon ta, saboda na ga Manzon Allah (ﷺ) ya yi maganar aurenta, don haka sai na juya mata baya na koma da baya-baya na ce: “Albishirinki Zainab, Manzon Allah (ﷺ) ya yi maganar aurenki.” Sai ta ce: ‘Ni ba abin da zan iya yi yanzu har sai na nemi zaɓin Ubangijina (watau ta yi *istikhara*).’ Sai ta tsaya a wurin sallarta ta yi salla ta yi addu’a. Sai Alƙur’ani ya sauko. Annabi (ﷺ) ya zo ya shiga wurinta ba tare da ya nemi izinin shiga ba....” [Muslim #1428].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Zainab ‘yar Jahshi ta kasance tana yi wa matan Annabi (ﷺ) alfahari da cewa: ‘Dukkanku iyayenku ne suka aurar da ku, ni kuwa Allah ne ya aurar da ni daga can saman sammai bakwai.’” [Bukhari #4721].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzo (ﷺ) cewa ba wani laifi da zai samu ko takuruwa game da auren abin da Allah ya halatta masa ya aura wadda ɗan riƙonsa ya taɓa aura ya saki, domin a wajen aiki da umarnin Allah ba shi ne farau ba, annabawa da suka gabace shi haka su ma suka yi. Wannan kuwa wani al’amari ne da Allah ya riga ya ƙaddara sai ya faru, saboda ba zaɓin Ma’aiki ne ba ko ra’ayinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffofin waɗannan manzanni da suka gabata da cewa su ne masu isar da saƙonnin da Allah ya aiko su da su zuwa ga al'ummunsu, kuma ba sa tsoron kowa sai Allah, don haka ba sa waiwayen abin da mutane suke faɗa yayin da suke aikata abin da Allah ya halatta musu. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi kaɗai ya isa ya kiyaye ayyukan bayinsa, domin ya yi musu hisabi a kansu, ya saka wa kowa gwargwadon aikinsa mai kyau ko mummuna.

Daga nan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dangantakar Manzonsa (ﷺ) da matsayinsa a cikin al’ummarsa da cewa, shi Annabi Muhammadu (ﷺ) bai kasance uban ɗaya daga cikin mazajen wannan al’umma ba, don haka ba shi ne mahaifin Zaidu ba ballantana auren matar da Zaidu ya saka ya haramta a gare shi. Sai dai matsayinsa a cikin wannan al’umma shi Manzon Allah ne zuwa ga mutane gaba ɗaya, kuma cikamakin annabawa, babu wani annabi da zai zo a bayansa, kuma Allah masanin komai ne.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Banu Isra’ila sun kasance annabawansu ne suke shugabantar su, duk sanda wani annabi ya rasu sai wani annabin ya maye gurbinsa, amma lalle ni babu wani annabi a bayana.” [Bukhari #3455 da Muslim #1842].

An karɓo daga Sauban (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle za a yi wasu manyan maƙaryata talatin a cikin al’ummata kowannensu yana riya cewa lalle shi annabi ne, to kuma ni ne cikamakin annabawa, a bayana babu wani annabi da zai zo....” [Abu Dawud #4252 da Tirmizi #2219].

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa wa Ali cewa: “Kai matsayinka a wurina kamar matsayin Haruna ne a wurin Musa, sai dai ni babu wani annabi a bayana.” [Tirmizi #3730].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar yawaita ambaton Allah safe da yamma.

2. Falalar imani da Allah, domin shi ne musabbabin samun yabo daga Allah da kyakkyawar addu’ar mala’iku.

3. Tabbatar da tashin alƙiyama.

4. Soyayyar Allah da mala’ikunsa ga muminai.

5. Sallama gaisuwar muminai ce a Aljanna.

Suratul Ahzab (41-44)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ ذِكۡرٗا كَثِيرٗا ٤١ وَسَبِّحُوهُ بُكۡرَةٗ وَأَصِيلٗا ٤٢ هُوَ ٱلَّذِي يُصَلِّي عَلَيۡكُمۡ وَمَلَٰٓئِكَتُهُۥ لِيُخۡرِجَكُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِۚ وَكَانَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ رَحِيمٗا ٤٣ تَحِيَّتُهُمۡ يَوۡمَ يَلۡقَوۡنَهُۥ سَلَٰمٞۚ وَأَعَدَّ لَهُمۡ أَجۡرٗا كَرِيمٗا ٤٤

41. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ambaci Allah ambato mai yawa.

42. Kuma ku yi tasbihi a gare Shi safe da yamma.

43. Shi ne wanda Yake yi muku salati da mala’ikunsa don Ya fitar da ku daga duffai zuwa haske, Allah kuwa Ya kasance Mai rahama ga muminai.

44. Gaisuwarsu a ranar da za su haɗu da Shi (ita ce) ‘*Salamun Alaikum*’. Ya kuma tanadar musu da lada na karamci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su yawaita ambaton Allah da harsunansu da zukatansu da gaɓoɓinsu, su kuma tsarkake shi daga dukkan tawaya da aibi ta hanyar yin tasbihi da hailala safe da yamma.

An karɓo daga Abud-Darda (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Yanzu ba na faɗa muku mafi alherin ayyukanku ba, mafi tsarkakarsu a wurin mamallakinku (Allah), mafi ɗaukakawa ga darajojinku, mafi alheri a kan bayar da sadakar zinari da azurfa, mafi alheri a kan ku haɗu da maƙiyanku ku sari wuyayensu su ma su sari wuyayenku?” Sahabbai suka ce: “Mene ne wannan aikin ya Manzon Allah?” Sai ya ce: “Ambaton Allah mai girma da buwaya.” [Ahmad #21702 da Tirmizi #3377].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Busur (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya ce wa Manzon Allah (ﷺ): “Ya Manzon Allah, hukunce-hukuncen Musulunci sun yi mini yawa, ka umarce ni da wani abu da zan ƙanƙame shi.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: “Kada harshenka ya gushe yana ɗanye shatab da ambaton Allah.” [Ahmad #17680 da 2329].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wata rahama da falala da ya yi wa muminai, da cewa shi ne yake yi musu salati, watau yake yin rahama da yabo gare su. Mala’ikunsa ma suna yi musu addu’a da nema musu gafarar Allah, domin Allah ya fitar da su daga duffan kafirci zuwa hasken imani. Allah ya tabbatar wa muminai cewa, shi mai rahama ne a gare su, don haka ba zai yi musu azaba ba idan har sun yi masa ɗa’a, sun yi aiki da umarninsa.
Sannan ya bayyana rahamarsa gare su a lahira yayin da zai shigar da su Aljanna; gaisuwarsu a ranar da za su haɗu da Ubangijinsu kuma ita ce *‘Salamun Alaikum*’, watau samun aminci da kuɓuta daga duk wani abin

ƙi. Kuma Allah ya tanadar musu wani lada mai karamci, wannan sakamako ne a kan biyayyar da suka yi gare shi da nisantar saɓa masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babban aikin Manzon Allah (ﷺ) shi ne albishir da gargaɗi.

2. Falalar kira zuwa ga Allah (da'awa) domin mafi muhimmancin ayyukan Annabi (ﷺ) da siffofinsa shi ne kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Nuni a kan cewa ya wajaba mai da'awa ya zamanto yana kira ne zuwa ga Allah ba zuwa ga kansa ba.

4. Shi kansa Annabi (ﷺ) ba shi ne yake shar'anta wa kansa abin da yake so ba, shi ma yana karɓar shari'a ne daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Duk abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi to haske ne tamkar fitila da yake haskaka duhu. Duk wanda ya bar shi to ya shigar da kansa cikin duffai da ba zai taɓa fita daga cikinsu ba.

6. Haramta biye wa kafirai da munafukai a kan duk abin da ya saɓa wa shiriyar Allah.

7. Ta'adar kafirai da munafukai ita ce su cutar da Annabi (ﷺ) da muminai.

8. Wajabcin yin haƙuri a kan cutarwar kafirai da munafukai da dogaro ga Allah shi kaɗai.

9. Bayani a kan cewa shi kansa Manzo (ﷺ) bai mallaki cutarwa ko amfanarwa ga kansa ko ga waninsa ba.

Suratul Ahzab (45-48)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَٰكَ شَٰهِدٗا وَمُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ٤٥ وَدَاعِيًا إِلَى ٱللَّهِ بِإِذۡنِهِۦ وَسِرَاجٗا مُّنِيرٗا ٤٦ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ بِأَنَّ لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ فَضۡلٗا كَبِيرٗا ٤٧ وَلَا تُطِعِ ٱلۡكَٰفِرِينَ وَٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَدَعۡ أَذَىٰهُمۡ وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلٗا ٤٨

45. Ya kai wannan Annabi, lalle Mu Mun aiko ka kana mai shaida, kuma mai albishir kuma mai gargaɗi.

46. Kuma mai kira zuwa ga Allah da izininsa, kuma fitila mai haskakawa.

47. Ka kuma yi wa muminai albishir cewa, suna da wata falala mai girma daga wurin Allah.

48. Kada kuma ka yi wa kafirai da munafukai ɗa'a, ka kuma bar cutarsu (da suke yi maka), ka kuma dogara ga Allah. Allah kuwa Ya isa Ya zama abin dogara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira Annabi (ﷺ) ya tunatar da shi nauyin da ya ɗora masa na manzanci zuwa ga mutane baki ɗaya, don ya zama mai shaida a kansu game da saƙon da ya isar musu, mai albishir ga muminai da tanadin da Allah ya yi musu na gidan Aljanna, mai kuma tsoratar da kafirai game da wuta wadda aka tanade ta domin waɗanda suka kafirce wa Allah da manzanninsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa cewa ya aiko shi don ya zama mai kira zuwa ga kaɗaita Allah da bauta da izininsa, ya kuma zama fitila mai haske da za ta haskaka wa mutane hanyar shiriya.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Wallahi an siffanta Annabi Muhammadu (ﷺ) a Attaura da wasu siffofinsa da suka zo a Alƙur’ani, an kirawo shi: ‘Ya kai wannan Annabi, lalle mu mun aiko ka don ka zama mai shaida mai albishir kuma mai gargaɗi, ka zamo kariya ga Larabawa ummiyyai. Kai bawana ne kuma manzona, na raɗa maka suna Al-Mutawakkilu (watau mai dogaro ga Allah).’ Shi ba mai kakkausan hali ba ne, ba mai ƙeƙasasshiyar zuciya ba, ba mai hayaniya a kasuwanni ba, ba ya rama mugunta da mugunta, sai dai ya yi afuwa, ya yi gafara. Allah ba zai karɓi ransa ba har sai ya miƙar da karkataccen addini da shi, watau su ce: [Babu abin bauta da gaskiya sai Allah], ya kuma buɗe makafin idanuwa da kuramen kunnuwa da rufaffun zukata da wannan Kalma ta Shahada.” [Bukhari #4838].
Allah kuma ya umarce shi da ya faɗa wa muminai waɗanda suka yi imani da Allah suka kuma yi kyawawan ayyuka, ya kuma yi musu albishir cewa suna da wata falala daga Allah mai girma wadda ta ƙunshi samun nasara a nan duniya da rabauta da gidan Aljanna a lahira.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi Manzonsa (ﷺ) a kan kada ya biye wa ta kafirai da munafukai game da abin da suke buƙata wanda ya saba wa shari’a, ya kuma umarce shi da ya kau da kansa daga gare su, watakila yin haka ya sanya su yi imani da abin da ya zo musu da shi na Musulunci. Ya kuma dogara ga Allah a cikin dukkan al’amuransa don Allah ya ba shi nasara a kan abokan gabarsa. Ya tabbatar masa cewa ya isa ya zama abin dogaro ga bayinsa cikin duk al’amuransu na duniya da na lahira.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman sha’anin saki, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sai da ya kirawo muminai da siffar imani sannan ya yi musu bayani a kansa, don ya nuna musu muhimmancinsa.

2. Saki ba ya tabbata sai bayan an ɗaura aure ba gabanin ɗaurin aure ba.

3. Halaccin yin saki kafin saduwa da matar da aka ɗaura wa aure.

4. Idan mutum ya saki amaryarsa kafin ya sadu da ita to babu idda a kanta. Sai dai yawancin malamai suna ganin idan har ya keɓanta da ita a ɗaki, to lalle za ta yi idda. Wannan shi ne abin da halifofin Manzon Allah huɗu suka yi hukunci da shi.

5. Wajabcin ba wa wadda aka saka wani abu da zai daɗaɗa mata rai kuma ya rage mata damuwa. Idan kuwa wadda aka saka an riga an yanka mata sadaki to sai a ba ta rabin sadakinta, kamar yadda ya zo a aya ta 237 cikin *Suratul Bakara*.

6. Wajabcin yin kyakkyawan saki, shi ne wanda babu cutarwa a cikinsa.

7. Idda haƙƙin miji ne a kan matarsa.

8. Saki yana hannun miji ne ba wani ba.

Suratul Ahzab (49)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا نَكَحۡتُمُ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ ثُمَّ طَلَّقۡتُمُوهُنَّ مِن قَبۡلِ أَن تَمَسُّوهُنَّ فَمَا لَكُمۡ عَلَيۡهِنَّ مِنۡ عِدَّةٖ تَعۡتَدُّونَهَاۖ فَمَتِّعُوهُنَّ وَسَرِّحُوهُنَّ سَرَاحٗا جَمِيلٗا ٤٩

49. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kuka auri mata muminai, sannan kuka sake su tun kafin ku sadu da su, to babu wata idda taku a kansu da za ku nemi cikar adadin (kwanakinta); to ku jiyar da su daɗi, kuma ku sake su kyakkyawan saki.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai wani hukunci ne da ya shafi aure da saki da iddar mata, watau idan sun auri muminai mata sai suka sake su tun kafin su sadu da su, to waɗannan mata babu idda a kansu da za su yi wa waɗannan mazaje da suka sake su; suna iya yin aurensu duk sanda suka ga dama. Wannan hukunci bai shafi matar da mijinta ya mutu ba bayan an ɗaura musu aure bai sadu da ita ba; ita wannan malamai sun haɗu a kan cewa za ta yi masa iddar takaba, watau zaman wata huɗu da kwana goma kafin ta yi wani aure.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mazajen da su ba su abin da zai daɗaɗa musu rai don su rage musu raɗaɗin sakin da aka yi musu, sannan su ƙyale su su koma ga iyayensu ba tare da sun cutar da su ba.

An karɓo daga Sahal ɗan Sa'ad da Abu Usaid (Allah ya ƙara masa yarda) cewa: "Lalle Annabi (ﷺ) ya auri Umaimatu 'yar Shurahilu, da ya shiga wurinta ya miƙa hannunsa gare ta sai ta nuna masa ba ta so, sai ya umarci Abu Usaid da ya shirya mata kayanta, ya kuma ba ta rigunan sawa biyu na farin kittani, (ya mayar da ita wurin iyayenta)". [Bukhari #5256].

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halattawa da haramtawa haƙƙin Allah ne.

2. Sadaki rukuni ne na aure.3. Rukunin mata 'ya'yan dangi huɗu da ya halatta ga namiji ya aura.

4. An halatta wa Annabi (ﷺ) auren wadda ta ba shi kanta da sharaɗin ta kasance mumina. Wannan yana daga cikin abubuwan da shi kaɗai ya keɓanta da su.

5. Duk hukuncin da ya tabbata ga Annabi (ﷺ) to ya tabbata ga al'ummarsa sai dai in wani dalili ya nuna saɓanin haka.

Suratul Ahzab (50)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ إِنَّآ أَحۡلَلۡنَا لَكَ أَزۡوَٰجَكَ ٱلَّٰتِيٓ ءَاتَيۡتَ أُجُورَهُنَّ وَمَا مَلَكَتۡ يَمِينُكَ مِمَّآ أَفَآءَ ٱللَّهُ عَلَيۡكَ وَبَنَاتِ عَمِّكَ وَبَنَاتِ عَمَّٰتِكَ وَبَنَاتِ خَالِكَ وَبَنَاتِ خَٰلَٰتِكَ ٱلَّٰتِي هَاجَرۡنَ مَعَكَ وَٱمۡرَأَةً مُّؤۡمِنَةً إِن وَهَبَتۡ نَفۡسَهَا لِلنَّبِيِّ إِنۡ أَرَادَ ٱلنَّبِيُّ أَن يَسۡتَنكِحَهَا خَالِصَةً لَّكَ مِن دُونِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۖ قَدۡ عَلِمۡنَا مَا فَرَضۡنَا عَلَيۡهِمۡ فِيٓ أَزۡوَٰجِهِمۡ وَمَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُمۡ لِكَيۡلَا يَكُونَ عَلَيۡكَ حَرَجٞۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٥٠

50. Ya kai wannan Annabi, lalle Mun halatta maka matanka waɗanda ka ba da sadakinsu, da kuma kuyanginka daga abin da Allah Ya ba ka na ganima, da 'ya'yan baffanka mata da 'ya'yan gwaggwaninka mata da 'ya'yan kawunka mata, da 'ya'yan yagwalgwalanka mata waɗanda suka yi hijira tare da kai, da kuma duk wata mace mumina, idan ta ba da kanta ga Annabi (shi) Annabin kuwa yana nufin ya aure ta, (wannan) keɓantacce ne a gare ka, ban da sauran muminai. Haƙiƙa Mun san abin da Muka ɗora musu game da matansu da kuma kuyanginsu, don kada a samu wata ƙuntatawa a kanka. Allah kuwa Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Annabinsa (ﷺ) nau'in matan da ya halatta masa

ya aura da ƙwaraƙwarai da suka halatta a gare shi. A cikin abubuwan da aka yi bayani akwai waɗanda sauran muminai suka yi tarayya da shi a cikinsu, akwai kuma abin da shi kaɗai ya keɓanta da shi.
Allah ya fara da cewa, ya halatta masa auren matansa waɗanda ya ba su sadakinsu. Wannan ya shafi duk wani Musulmi, yana iya auren wadda ya biya sadakinta. Sannan da ƙwaraƙwaran da ya mallaka yana iya saɗaka da su idan yana so. Wannan ma sauran muminai sun yi tarayya da shi a ciki, watau su ma suna iya yin saɗaka da kuyanginsu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa cewa ya halatta masa auren 'ya'yan baffanninsa maza da na gwaggwanninsa mata da 'ya'yan kawunnansa maza da na innoninsa mata waɗanda suka yi hijira zuwa Madina tare da shi. Sauran muminai ma sun yi tarayya da shi a wannan hukunci.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa cewa, ya halatta masa auren duk wata mace mumina wadda za ta ba da kanta kyauta gare shi, idan yana son aurenta to zai iya auren ta ba tare da sadaki ko waliyyi ko shaidu ba. Wannan hukunci ya keɓanta da shi ne shi kaɗai ban da sauran muminai, su kam dole ne aurensu sai da sadaki da waliyyi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ya san abin da ya wajabta wa muminai game da adadin matan da ƙowannensu ya halatta ya aura, watau ya ƙayyade musu auren iya mata huɗu kada su wuce su. Ya kuma san abin da ya shar'anta musu dangane da kuyanginsu, za su iya saɗaka da ko guda nawa ne ba tare da ƙayyadewar adadi ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna masa dalilin da ya sanya ya halatta masa abubuwan da ya ambata, watau ya yi haka ne don kada ya ƙuntata masa ko ya wahalar da shi, Allah kuma ya tabbata mai gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai rahama ne gare su.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba wa Annabi (ﷺ) zaɓi tsakanin rabon kwana ga matansa ko barinsa. Wannan halacci ne da ya keɓanta da shi (ﷺ) ban da sauran al'ummarsa.

2. Ya halatta ga mutum ya koma wa haƙƙinsa bayan ya haƙura da shi idan haƙƙin ya kasance mai sabuntuwa ne. Amma idan ba mai sabuntuwa ne ba, to idan ya sarayar da shi a karon farko to ya saraya gaba ɗaya.

3. Yana da kyau matuƙa mumini ya yi abin da zai shigar wa da ɗan'uwansa mumini farin ciki a zuciyarsa da kawar masa da damuwa.

4. Abin da yake cikin zuciyar mutum wanda ba ya da iko a kansa Allah ba ya kama shi da laifinsa, kamar soyayyar mata.

Suratul Ahzab (51)
*تُرۡجِي مَن تَشَآءُ مِنۡهُنَّ وَتُـٔۡوِيٓ إِلَيۡكَ مَن تَشَآءُۖ وَمَنِ ٱبۡتَغَيۡتَ مِمَّنۡ عَزَلۡتَ فَلَا جُنَاحَ عَلَيۡكَۚ ذَٰلِكَ أَدۡنَىٰٓ أَن تَقَرَّ أَعۡيُنُهُنَّ وَلَا يَحۡزَنَّ وَيَرۡضَيۡنَ بِمَآ ءَاتَيۡتَهُنَّ كُلُّهُنَّۚ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا فِي قُلُوبِكُمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَلِيمٗا٥١

51. Ka dakatar da duk wadda ka ga dama daga cikinsu, ka kuma jawo duk wadda ka ga dama; (duk) wadda kuwa ka nema daga waɗanda ka dakatar, to babu wani laifi a kanka. (Yin) wannan kuwa shi ya fi kusantar da kwanciyar ransu da kuma rashin yin baƙin ciki, su kuma yarda da duk abin da ka ba su dukkaninsu. Allah kuwa Yana sane da abin da yake cikin zukatanku. Allah kuwa Ya kasance Masani ne, Mai haƙuri.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya keɓance Annabi (ﷺ) da wani hukunci dangane da zamantakewarsa ta aure da matansa, watau ya ba shi damar ya gudanar da mu'amalar aure da su ba tare

da wajabta masa rabon kwana a tsakanninsu ba, kamar yadda ya wajabta wa al'ummarsa. Ya halatta masa ya dakatar da kwanan wadda ya ga dama daga cikin matansa, ya jawo wadda ya ga dama; idan kuma ya so ya jawo kwanan wadda ya dakatar to yana iya yin hakan babu wani laifi a kansa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya ba shi wannan zaɓi ne don shi ne zai kwantar wa matansa hankali, kuma su yarda da abin da ya ba wa kowace ɗaya daga cikinsu, domin sun tabbatar ba zai hana musu haƙƙoƙinsu ba ko ya ƙi yi musu adalci.
An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara masa yarda) ta ce: "Bayan wannan ayar ta (51) ta sauka, Annabi (ﷺ) ya kasance yana neman izinin ɗaya daga cikinmu a ranar kwananta (watau ta bar wa 'yar'uwarta)." Sai Mu'azatu ta tambayi A'isha cewa: "To ke me kike faɗa masa?" Sai ta ce: "Nakan ce masa: Ni ba zan so in fifita wata a kaina dangane da kai ba, ya Manzon Allah." [Bukhari #4789].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ya san abin da yake cikin zukatan mazaje na karkata ga wasu matan su bar wasu, domin ya san abin da yake cikin zukatan bayinsa, shi kuma mai haƙuri ne ba ya gaggauto da uƙuba ga wanda ya saba masa, yakan ba shi damar tuba domin ya yafe masa.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramta wa Manzon Allah (ﷺ) sakin wata daga cikin matansa don ya auri wata bayan sun zaɓi Allah da Manzonsa da gidan lahira. Hakanan an hana shi auren wata mata bayan waɗanda aka ambata a aya ta 50.

2. Zaman Annabi (ﷺ) ƙarƙashin inuwar shari'ar Allah, ana halatta masa ana kuma haramta masa, don haka babu wanda zai kai matakin da hukunce-hukuncen shari'a za su sauka daga kansa.

3. Bayanin babban matsayin matan Annabi (ﷺ) da zaɓar su da Allah ya yi don su zama matansa a Aljanna.

4. Halaccin mutum ya auri mace don kyanta, musamman idan mai addini ne.

Suratul Ahzab (52)
لَّا يَحِلُّ لَكَ ٱلنِّسَآءُ مِنۢ بَعۡدُ وَلَآ أَن تَبَدَّلَ بِهِنَّ مِنۡ أَزۡوَٰجٖ وَلَوۡ أَعۡجَبَكَ حُسۡنُهُنَّ إِلَّا مَا مَلَكَتۡ يَمِينُكَۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ رَّقِيبٗا ٥٢

52. Bayan (waɗannan) wasu mata ba su halatta gare ka ba, ko kuma ka musanya waɗansu (matan) da su, ko da kuwa kyansu ya ƙayatar da kai, sai dai abin da ka mallaka na kuyangi. Allah kuwa Ya kasance Mai lura ne da komai.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tagomashin da ya yi wa matan Manzon Allah (ﷺ) bayan an ba su zaɓi tsakanin zama da shi da kuma ƙyale-ƙyalen duniya, sun zaɓi Allah da Manzonsa da gidan lahira. To sai Allah ya faɗa wa Manzo (ﷺ) cewa bai halatta ba gare shi ya sake auren wasu mata ban da waɗannan da suke tare da shi, kuma bai halatta ya saki wasu daga cikinsu ba domin ya auro wasu matan ya cike gurbi da su, ko da kuwa ya ga wadda kyanta ya ƙayatar da shi ya yi nufin auren ta, Allah bai ba shi izini ba. Amma ya halatta gare shi ya riƙi ƙwaraƙwarai daga cikin kuyangin da yake mallaka ba tare da an ƙayyade masa wani adadi ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi mai lura ne da komai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin neman izini yayin shiga gidan wani.

2. Amsa gayyatar cin abinci idan an gayyaci mutum.

3. Rashin dacewar zama gidan wani domin jiran dahuwar abinci sai dai idan shi ya buƙaci hakan.

4. Haramcin aikata abin da zai cuci wani, ko da ba zai iya magana ba.

5. Annabi (ﷺ) mutum ne kamar sauran mutane, shi ma yana cutuwa da abin da mutane suke cutuwa da shi, sai dai shi ya fi kowa juriya da haƙuri.

6. Tsananin kunyar Manzon Allah (ﷺ) da yawan karamcinsa.

7. Halaccin magana da matan Manzon Allah (ﷺ) ta bayan shamaki.

8. Wajabcin tsarkake zukata daga duk wasu miyagun aƙidu da miyagun ɗabi'u.

9. Haramcin auren matan Annabi (ﷺ) a bayansa.

10. Haramcin cutar da Annabi (ﷺ).

Suratul Ahzab (53-54)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَدۡخُلُواْ بُيُوتَ ٱلنَّبِيِّ إِلَّآ أَن يُؤۡذَنَ لَكُمۡ إِلَىٰ طَعَامٍ غَيۡرَ نَٰظِرِينَ إِنَىٰهُ وَلَٰكِنۡ إِذَا دُعِيتُمۡ فَٱدۡخُلُواْ فَإِذَا طَعِمۡتُمۡ فَٱنتَشِرُواْ وَلَا مُسۡتَـٔۡنِسِينَ لِحَدِيثٍۚ إِنَّ ذَٰلِكُمۡ كَانَ يُؤۡذِي ٱلنَّبِيَّ فَيَسۡتَحۡيِۦ مِنكُمۡۖ وَٱللَّهُ لَا يَسۡتَحۡيِۦ مِنَ ٱلۡحَقِّۚ وَإِذَا سَأَلۡتُمُوهُنَّ مَتَٰعٗا فَسۡـَٔلُوهُنَّ مِن وَرَآءِ حِجَابٖۚ ذَٰلِكُمۡ أَطۡهَرُ لِقُلُوبِكُمۡ وَقُلُوبِهِنَّۚ وَمَا كَانَ لَكُمۡ أَن تُؤۡذُواْ رَسُولَ ٱللَّهِ وَلَآ أَن تَنكِحُوٓاْ أَزۡوَٰجَهُۥ مِنۢ بَعۡدِهِۦٓ أَبَدًاۚ إِنَّ ذَٰلِكُمۡ كَانَ عِندَ ٱللَّهِ عَظِيمًا ٥٣ إِن تُبۡدُواْ شَيۡـًٔا أَوۡ تُخۡفُوهُ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمًا ٥٤

53. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku shiga gidajen Annabi sai idan an yi muku izini zuwa (cin) abinci, alhali ba tare da kuna jiran dahuwarsa ba, sai dai kuma idan aka kira ku, to ku shiga, sannan idan kuka ci sai ku fice, ba tare da yin wata hira ta ɗebe kewa ba. Lalle wannan ya kasance yana cutar Annabi, sai yakan ji kunyar ku; Allah kuwa ba Ya jin kunyar (faɗar) gaskiya. Idan kuma za ku tambaye su (wato matan Annabi) wani abu na amfani, sai ku tambaye su ta bayan shamaki. Yin wannan shi ya fi tsarki ga zukatanku da kuma zukatansu. Kuma bai kamace ku ba ku cuci Manzon Allah ko kuma ku auri matansa a bayansa har abada. Lalle (yin) wannan ya kasance abu mai girma a wurin Allah.

54. Idan kuma kuka bayyana wani abu ko kuka ɓoye shi, to Allah Ya kasance Masanin komai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana koya wa muminai ladabin shiga gidan Manzon Allah da kuma ladabin da za su yi wurin magana da matansa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana su shiga gidan Manzon Allah (ﷺ) sai bayan an yi musu izinin shiga domin su ci abinci, ya kuma hana su zama suna jiran dahuwar abincin. Amma idan Manzon Allah (ﷺ) ne ya kirawo su cin abinci a gidansa to suna iya shiga, kuma da zarar sun gama cin abinci sai su watse kowa ya kama gabansa, kada su zauna su dasa hirar daɓe ko da a tsakaninsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana dalilin wannan hani da ya yi musu da cewa zamansu su daɗe a gidansa suna jiran dahuwar abinci, ko bayan sun ci su zauna suna hira, al'amari ne da yake cutar da Annabi (ﷺ), domin yana hana shi walwala da sakewa a gidansa tare da iyalansa, shi kuma yana jin kunyar ya yi magana a kai, Allah kuwa ba ya jin kunyar faɗar gaskiya ga kowane ne.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Lokacin da Annabi (ﷺ) ya auri Zainab 'yar Jahshi, ya gayyaci mutane ya shirya musu abinci suka ci, to bayan sun gama sai suka zauna suna ta hira, sai Annabi

(ﷺ) ya yunƙura kamar zai tashi don su gani su ma su tashi, amma sai suka ƙi tashi. Lokacin da ya ga haka sai shi ya tashi, to ganin haka sai wasu daga cikinsu suka tashi suka fita, amma sai mutum uku suka ci gaba da zama suna hira, sai Annabi (ﷺ) ya zo don ya shiga wurin matarsa Zainab sai ya sami waɗannan mutane zaune suna ta hira, (sai ya koma) sannan su kuma suka tashi suka fita. Sai na je na faɗa wa Annabi (ﷺ) cewa mutanen nan fa sun tafi, sai ya zo ya shiga wurin matarsa, ya saki shamaki tsakanina da shi, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar." [Bukhari #4791 da Muslim #1428].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya koya wa muminai yadda za su yi magana da matan Annabi (ﷺ) idan za su buƙaci wani abin a wurinsu, da cewa, idan suna buƙatar wani abin amfani a wurinsu to su tambaye su ta bayan shamaki, kada su nemi ganin su ido-da-ido, don tsare mutuncin Annabi (ﷺ). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa dalilin kafa musu wannan doka shi ne su sami tsarkin zuciya su da matan gaba ɗaya, don haka Shaiɗan ba zai sami wata kafa ya sanya wani mummunan wasiwasi a zukatansu ba.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Umar ya ce wa Annabi (ﷺ): "Ya Manzon Allah, muminan ƙwarai da waɗanda ba na ƙwarai ba duk suna shiga gidanka, da a ce ka umarci (matanka) iyayen muminai su sanya shamaki, (watau tsakaninsu da maza)." sai wannan ayar ta sauka." [Bukhari #4790].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa bai kamace su ba ko kaɗan su riƙa aikata abin da zai cutar da Annabi (ﷺ), kamar daɗewa a gidansa suna hira. Hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haramta musu auren matansa (ﷺ) bayan rasuwarsa, domin su matansa ne na Aljanna, sannan iyayen muminai ne, mutum kuwa ba zai auri uwarsa ba. Allah ya ƙara tabbatar musu da cewa cutar da Annabi (ﷺ) ko auren wata daga cikin matansa bayan rasuwarsa babban lamari ne a wurin Allah, domin zunubinsa yana da girma ainun.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi bayinsa da cewa, duk abin da suka bayyana na ayyukansu ko suka ɓoye a zukatansu, to Allah masanin komai ne, babu abin da zai ɓuya a wajensa, zai kuma yi musu sakayya a kai.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bai zama wajibi ba mace ta kange kanta daga waɗanda aka ambata a wannan ayar.

2. Duk wanda aure da shi haramun ne har abada, to shi ne ake kira 'muharrami', ban da wanda aka haramta aure da shi a wani ƙayyadadden lokaci.

3. Bai zama wajibi mace ta katange kanta daga 'yar'uwarta mace ba.

Suratul Ahzab (55)

لَّا جُنَاحَ عَلَيۡهِنَّ فِيٓ ءَابَآئِهِنَّ وَلَآ أَبۡنَآئِهِنَّ وَلَآ إِخۡوَٰنِهِنَّ وَلَآ أَبۡنَآءِ إِخۡوَٰنِهِنَّ وَلَآ أَبۡنَآءِ أَخَوَٰتِهِنَّ وَلَا نِسَآئِهِنَّ وَلَا مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُنَّۚ وَٱتَّقِينَ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدًا ٥٥

55. Babu laifi a kansu (matan) game da iyayensu maza (su gan su kuma su yi magana da su ba tare da shamaki ba) da kuma 'ya'yansu maza da 'ya'uwansu da 'ya'yan 'yan'uwansu maza da 'ya'yan 'yan'uwansu mata, da kuma matansu da bayinsu. Ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Ya kasance Mai ganin komai ne.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai mata waɗanda za su iya magana da su ba tare da wani shamaki a tsakaninsu ba da cewa, babu laifi ga iyayensu maza su gan su ko su yi magana da su, hakanan ‘ya’yansu maza da ‘yan’uwansu maza da ‘ya’yan ‘yan’uwansu maza da ‘ya’yan ‘yan’uwansu mata waɗanda suka haɗa dangantaka da su ta haihuwa ko ta shayarwa, da mata muminai ‘yan’uwansu, da bayinsu maza waɗanda suka mallake su cikakkiyar mallaka.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su kiyaye dokokin Allah a koyaushe a kuma kowane hali, domin shi mai ganin duk ayyukansu ne na sarari da na ɓoye, zai kuma yi musu sakayya a kansu.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman martabar Annabi (ﷺ) a wurin Allah da mala’ikunsa.

2. Falalar salati ga Manzon Allah (ﷺ) domin koyi ne da Allah da mala’iku.

3. Umarni da yi wa Annabi (ﷺ) salati.

4. Abin da ake buƙata a wurin mumini shi ne ya yi wa Annabi (ﷺ) salati da furucin bakinsa ba da zuciya kaɗai ba.

Suratul Ahzab (56)

إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِيِّۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ صَلُّواْ عَلَيۡهِ وَسَلِّمُواْ تَسۡلِيمًا ٥٦

56. Lalle Allah da mala’ikunsa suna yin salati ga Annabi. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi salati a gare shi, kuma ku yi sallama mai yawa.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman darajar Manzonsa (ﷺ) a wajensa da sauran mala’ikunsa, da cewa shi kansa Allah yana yi masa salati, watau yana yabon sa a cikin mala’ikunsa domin ƙaunar sa da yake yi, hakanan su ma mala’iku duka suna yi wa Manzon Allah (ﷺ) salati, watau suna yi masa kyakkyawar addu’a da roƙa masa ƙarin daraja a wurin Allah. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su ma su yi masa salati da sallama mai yawa, domin koyi da Allah da mala’ikunsa, su kuma ba shi wani ɓangare na haƙƙinsa a kansu.

An karɓo daga Ka’abu ɗan Ujra (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Sahabbai sun ce wa Manzon Allah (ﷺ): “Ya Manzon Allah, mun san yadda za mu yi maka sallama, to amma yaya za mu yi maka salati?” Sai ya ce: “Ku ce: “Ya Allah ka yi salati ga Muhammadu da iyalan Muhammadu, kamar yadda ka yi salati ga iyalan Ibrahimu, lalle kai sha yabo ne mai girma. Ya Allah ka yi wa Muhammadu albarka da iyalan Muhammadu, kamar yadda ka yi albarka ga iyalan Ibrahimu, lalle kai sha yabo ne mai girma.” [Bukhari #4797].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk wanda ya yi mini salati ɗaya, to Allah zai yi masa salati goma.” [Muslim #408].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cutar da Annabi (ﷺ) yana daga cikin manya-manyan zunubai.

2. Cutar da Manzon Allah (ﷺ) daidai yake da cutar da Allah ta fuskar haramci.

3. Haramun ne mumini ya cuci ɗan’uwansa mumini ba tare da wani haƙƙi ba.

4. Cutar da mumini da haƙƙi, watau da wani laifin da ya aikata kamar yi masa haddin zina, ko sata da makamancinsa, ba haramun ne ba, zartar da hukuncin Allah ne a kansa.

Suratul Ahzab (57-58)
إِنَّ ٱلَّذِينَ يُؤۡذُونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَأَعَدَّ لَهُمۡ عَذَابٗا مُّهِينٗا ٥٧ وَٱلَّذِينَ يُؤۡذُونَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ بِغَيۡرِ مَا ٱكۡتَسَبُواْ فَقَدِ ٱحۡتَمَلُواْ بُهۡتَٰنٗا وَإِثۡمٗا مُّبِينٗا ٥٨

57. Lalle waɗanda suke cutar Allah da Manzonsa, to Allah Ya la’ance su a duniya da lahira, Ya kuma tanadar musu azaba mai wulaƙantarwa.

58. Waɗanda suke cutar muminai maza da muminai mata ba tare da sun yi laifi ba, to haƙiƙa sun ɗauki nauyin ƙage da kuma zunubi bayyananne.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman martabar Annabi (ﷺ) sai kuma ya yi gargaɗi mai tsanani ga waɗanda suke cutar da shi da miyagun maganganunsu ko da ayyukansu, da cewa lalle waɗanda suke cutar da Allah da Manzonsa (ﷻ), to ya la’ance su a duniya da lahira, watau ba su babu samun rahamarsa, ya kuma tanadar musu azabar wulaƙanci a lahira.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, su ma masu cutar da muminai maza da muminai mata ba tare da sun yi musu wani laifi ba, to su sani cewa sun ɗaukar wa kansu laifin wani ƙage da zunubi bayyananne.

An karɓo daga Sa’idu ɗan Zaid (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Mafi munin riba, mutum ya ci mutuncin ɗan’uwansa Musulmi ba tare da wani haƙƙi ba.” [As-Shashi, *Al-Musnad* #208].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Shin ko kun san abin da ake ce wa giba (yi da mutum)?” Sai suka ce: “Allah da Manzonsa ne suka fi sani.” Sai ya ce: “Ka ambaci ɗan’uwanka da abin da yake ƙi.” Sai aka ce: “Idan yana da abin da muke faɗa fa?” Sai ya ce: “Idan yana da abin da kake faɗa a kansa, to ka yi gibar sa, idan kuwa ba ya da shi, to ka yi masa ƙage.” [Muslim #2589].

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin sanya lullubi ga ‘ya’ya mata.

2. Alhaki ne a kan kowane magidanci ya umarci matansa da ‘ya’yansa mata da matan da suke ƙarƙashin kulawarsa su riƙa yin lullubi yayin da za su fita.

3. Sanya lullubi al’adar matan sahabbai ce.

4. Har koyaushe shari’a tana son ‘ya mace ta riƙa ɓoye kyanta da kwalliyarta ga waɗanda bai halatta gare su su gan ta cikin kwalliya ba, ko su ga wani sashi na jikinta wanda shari’a ba ta amince mace ta bayyana shi ba gare su.

5. Muhimmancin da Musulunci ya bai wa ‘ya mace ta hanyar kare ta daga duk wani abu da zai cutar da ita.

6. Hijabi mutuncin ‘ya mace ne.

Suratul Ahzab (59)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ قُل لِّأَزۡوَٰجِكَ وَبَنَاتِكَ وَنِسَآءِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ يُدۡنِينَ عَلَيۡهِنَّ مِن جَلَٰبِيبِهِنَّۚ ذَٰلِكَ أَدۡنَىٰٓ أَن يُعۡرَفۡنَ فَلَا يُؤۡذَيۡنَۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٥٩

59. Ya kai wannan Annabi, faɗa wa matanka da ‘ya’yanka mata da kuma matan muminai (cewa) su sanya lullubinsu. Wannan shi ya fi sanya wa a gane su, don kada a cuce su. Allah kuma Ya kasance Mai gafara ne, Mai rahama.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nemi Annabinsa (ﷺ) da ya umarci matansa da ‘ya’yansa mata da matan muminai su saki lullubinsu a jikinsu lokacin da suka fito daga gidajensu, domin a tantance tsakaninsu da mata marasa kamun kai, don kada a cutar da su kamar yadda akan yi wa marasa kamun kai. Allah ya tabbatar masa da cewa shi mai gafara ne ga bayinsa masu laifi idan sun tuba, mai jin ƙan su ne.

An karbo daga Ummu Salama (Allah ya ƙara masa yarda) ta ce: “Lokacin da wannan ayar ta sauka matan mutanen Madina sukan fita kai ka ce hankaku ne a kan kawunansu saboda nutsuwa, suna lulluɓe da baƙaƙen lullubi.” [Abu Dawud #410].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan munafuncin munafuki ya fito sarari ya bayyana gabarsa da ƙiyayyarsa ga muminai to yana da kyau a yi masa hukuncin da ya dace da mugun halinsa.

2. Gargaɗi da jan kunne game da munafunci da yaɗa labaran ƙarya a tsakanin muminai da aikata miyagun ɗabi’u waɗanda suke jefa zukata cikin cuta mai muni.

3. Halaccin kora ko tsare wanda barin sa cikin jama’a zai cutar da su.

Suratul Ahzab (60-62)
۞لَّئِن لَّمۡ يَنتَهِ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ وَٱلۡمُرۡجِفُونَ فِي ٱلۡمَدِينَةِ لَنُغۡرِيَنَّكَ بِهِمۡ ثُمَّ لَا يُجَاوِرُونَكَ فِيهَآ إِلَّا قَلِيلٗا ٦٠ مَّلۡعُونِينَۖ أَيۡنَمَا ثُقِفُوٓاْ أُخِذُواْ وَقُتِّلُواْ تَقۡتِيلٗا ٦١ سُنَّةَ ٱللَّهِ فِي ٱلَّذِينَ خَلَوۡاْ مِن قَبۡلُۖ وَلَن تَجِدَ لِسُنَّةِ ٱللَّهِ تَبۡدِيلٗا ٦٢

60. Tabbas munafukai da waɗanda suke da raunin imani a zukatansu da kuma masu yaɗa ƙarairayi a Madina, idan ba su bari ba, lalle za Mu cuna ka a kansu (don ka hukunta su), sannan kuma ba za su zauna da kai a cikinta ba sai ɗan lokaci ƙanƙani.

61. (Su) la’anannu ne; duk inda aka gamu da su a kama su, kuma a yi musu mummunan kisa.

62. (Wannan) Sunnar Allah ce ga waɗanda suka gabata a da; ba kuma za ka sami wani canji ba game da sunnar Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi munafukai waɗanda suke cike da hassada da ƙiyayya ga muminai, da waɗanda zukatansu suke ɗauke da cutar sha'awa da waɗanda suke baza labaran ƙarya a Madina don su raba kan muminai, Allah ya ja kunnuwansu da cewa idan ba su daina miyagun halayensu ba, to lalle zai umarci Annabi (ﷺ) da ya hukunta su, zai kuma ɗora shi a kansu har ya fi ƙarfinsu. Daga wannan ranar kuwa zaman garin Madina zai yi musu wuya sai na ɗan lokaci kaɗan, domin za a kore su daga wannan gari saboda yawaitar ɓarnarsu da sharrinsu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa su la'anannu ne waɗanda ba su ba rahamar Allah, kuma duk inda aka gamu da su sai a kama su a yi musu mummunan kisa saboda munafuncinsu da yaɗa ɓarna da suke yi a bayan ƙasa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wannan sunnarsa ce mai gudana a kan munafukai duk sanda suka bayyana munafuncinsu a fili, sunnar Allah kuwa tabbatacciya ce ba za ka sami wani canji ba game da ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ne kaɗai ya keɓanta da sanin lokacin tashin alƙiyama, hatta Manzon Allah (ﷺ) shi ma bai sani ba.
2. Kusantowar lokacin tashin alƙiyama.

3. Kafirci abu ne da ke jawo wa bawa la'anar Allah.

4. Kafirai za su dawwama a wuta har abada.

5. Bayanin tsananin azabar kafirai a lahira.

6. Babu abin da zai kuɓutar da bawa daga azabar Allah sai ɗa'a ga Allah da kuma Manzonsa (ﷺ).

7. Hatsarin bin shugabanni da manyan mutane ido-rufe a kan ɓata da kauce wa gaskiya.

8. Biyayya ga shugabanni a kan ɓata ba uzuri ba ne a wurin Allah.

9. Duk haɗuwar da ba a gina ta ba a kan gaskiya ƙarshenta yana zama ƙiyayya ce mai muni.

10. Duk wanda ya riƙe wani ba Allah ba, ya bi shi a kan abin da ya saɓa wa Allah, to ba zai yi masa wani amfani a lahira ba.

Suratul Ahzab (63-68)
يَسۡـَٔلُكَ ٱلنَّاسُ عَنِ ٱلسَّاعَةِۖ قُلۡ إِنَّمَا عِلۡمُهَا عِندَ ٱللَّهِۚ وَمَا يُدۡرِيكَ لَعَلَّ ٱلسَّاعَةَ تَكُونُ قَرِيبًا ٦٣ إِنَّ ٱللَّهَ لَعَنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ وَأَعَدَّ لَهُمۡ سَعِيرًا ٦٤
خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ لَّا يَجِدُونَ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ٦٥ يَوۡمَ تُقَلَّبُ وُجُوهُهُمۡ فِي ٱلنَّارِ يَقُولُونَ يَٰلَيۡتَنَآ أَطَعۡنَا ٱللَّهَ وَأَطَعۡنَا ٱلرَّسُولَا ٦٦ وَقَالُواْ رَبَّنَآ إِنَّآ
أَطَعۡنَا سَادَتَنَا وَكُبَرَآءَنَا فَأَضَلُّونَا ٱلسَّبِيلَا ٦٧ رَبَّنَآ ءَاتِهِمۡ ضِعۡفَيۡنِ مِنَ ٱلۡعَذَابِ وَٱلۡعَنۡهُمۡ لَعۡنٗا كَبِيرٗا ٦٨

63. Mutane suna tambayar ka game da (ranar) alƙiyama; ka ce (da su): "Saninta a wajen Allah kawai yake." Ba ka sani ba ko watakila alƙiyamar za ta kasance kusa.

64. Lalle Allah Ya la'anci kafirai Ya kuma tanadar musu da (wutar) Sa'ira.

65. Masu dawwama ne a cikinta har abada; ba kuma za su sami wani majiɓinci ko mataimaki ba.

66. A ranar da za a riƙa jujjuya fuskokinsu cikin wuta, suna cewa: “Kaiconmu, ina ma da mun bi Allah mun bi Manzo!”

67. Suka kuma ce: “Ya Ubangijinmu, lalle mu mun bi shugabanninmu da manyanmu sai suka ɓatar da mu hanya.

68. “Ya Ubangijinmu, Ka ba su azaba riɓi biyu, Ka kuma la’ance su babbar la’ana.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mushirikai sun riƙa yi wa Annabi (ﷺ) tambayar cewa ya faɗa musu yaushe ne ranar alƙiyama za ta zo, domin su nuna cewa ƙarya yake yi da ya ce akwai ranar alƙiyama. Su ma Yahudawa sun matsa wa Annabi lamba kan sai ya faɗa musu lokacin, don kawai su ce sun ƙure shi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya faɗa musu cewa, shi ba shi da wata masaniya game da lokacin zuwanta, wannan ilimi yana ga Allah shi kaɗai, shi ya bar wa kansa sani, kuma tana yiwuwa ma alƙiyamar ta kusa zuwa.
Sannan Allah ya la’anci kafirai, ya nesanta su daga rahamarsa, ya kuma yi musu tanadin wutar Jahannama mai tsananin ƙuna a lahira wadda za su dawwama har abada a cikinta kuma ba za su sami wani majiɓinci ko mataimaki ba wanda zai fito da su daga wannan mummunar azabar.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mawuyacin halin da za su shiga a wannan ranar, domin a nan za a riƙa jujjuya fuskokinsu a cikin wuta kamar ana dahuwar nama a cikin tukunya, su kuma suna ta ihu suna nadama, suna cewa ina ma dai sun bi Allah sun aikata abin da ya umarce su, sun guje wa abin da ya hane su, kuma sun bi Manzon Allah a kan abin da ya zo musu da shi daga Allah.
Daga nan sai su fara neman hujjar da za su ba wa Allah don ya tserar da su daga wannan azaba da suke ciki, to amma hujjar da suka kawo mai matuƙar rauni ce, domin cewa suke yi su fa sun bi shugabanninsu ne da manyansu sai suka jefa su cikin ɓata. Don haka sai su roƙi Allah ya azabtar da shugabanninsu ninki biyu, watau azabar ɓatan da suka yi da kuma ɓatar da wasu da suka yi, kuma ya la’ance su ya nesanta su daga rahamarsa la’ana mai girma.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin cutar da Annabi (ﷺ) da maganar baki ko a aikace.

2. Yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ba wa annabawansa kariya yana wanke su daga kowace irin tuhuma da za a yi musu.

3. Babban abin lura shi ne bawa ya samu daraja a wurin Allah, shi ne abin nema. Darajar bawa a wurin Ubangijinsa kuwa yana samun ta ne ta hanyar bauta masa da tsayawa a kan shari’arsa.

Suratul Ahzab (69)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ ءَاذَوۡاْ مُوسَىٰ فَبَرَّأَهُ ٱللَّهُ مِمَّا قَالُواْۚ وَكَانَ عِندَ ٱللَّهِ وَجِيهٗا ٦٩

69. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku zamanto kamar waɗanda suka cuci Musa sai Allah Ya wanke shi daga abin da suka faɗa (a kansa). Ya kuma kasance mai alfarma ne a wurin Allah.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira muminai ya gargaɗe su da kada su yi koyi da Yahudawa waɗanda suka riƙa cutar da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da yi masa miyagun

maganganu iri-iri, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wanke shi daga aibata shi da suka yi, domin ya kasance mai daraja ne a wurinsa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Banu Isra’ila sun kasance suna taruwa suna yin wanka tsirara suna kallon junansu, amma shi Musa sai ya zamanto yana yin wankansa shi kaɗai. Sai suka ce: ‘Babu abin da yake hana shi wanka tare da mu sai don yana da gwaiwa.” Sai wata rana ya tafi yana wanka, ya ɗora tufafinsa a kan wani dutse, sai dutsen ya gudu da tufafinsa, sai Musa ya fita ya bi shi yana cewa: ‘Kai dutse tufafina! kai dutse tufafina!!.’ Yana cikin haka sai Banu Isra’ila suka gan shi, nan take suka ce: ‘Wallahi Musa ba ya da wata cuta tare da shi.’ Sai dutse ya tsaya Musa ya ɗauki tufafinsa sai ya riƙa dukan wannan dutsen.” [Bukhari #3404 da Muslim #339].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Annabi (ﷺ) ya yi wani rabo sai wani mutum ya ce: “Wannan rabon ba a nufi Allah da shi ba.” Sai Abdullahi ɗan Mas’ud ya garzayo ya faɗa wa Annabi (ﷺ) abin da mutumin nan ya faɗa, sai Annabi (ﷺ) ya yi fushi har sai da fushin ya bayyana a fuskarsa sannan ya ce: “Allah ya ji ƙan Musa, haƙiƙa an cutar da shi fiye da haka amma ya yi haƙuri.” [Bukhari #3405 da Muslim #1062].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarnin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi na cewa muminai su faɗi maganar da take daidai ya ƙunshi faɗin duk wata magana ta alheri kamar ambaton Allah, da bitar ilimi, da umarni da kyakkyawan aiki da hani ga mummuna, da yin sulhu tsakanin mutane da sauransu.

2. Babu mai samun rabauta a lahira sai wanda ya bi Allah da Manzonsa a nan duniya.

Suratul Ahzab (70-71)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَقُولُواْ قَوۡلٗا سَدِيدٗا ٧٠ يُصۡلِحۡ لَكُمۡ أَعۡمَٰلَكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۗ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدۡ فَازَ فَوۡزًا عَظِيمًا ٧١

70. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku faɗi Magana wadda take daidai ce.

71. Zai kyautata muku ayyukanku, Ya kuma gafarta muku zunubanku. Duk kuwa wanda ya bi Allah da Manzonsa, to haƙiƙa ya rabauta rabauta mai girma.

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su kiyaye dokokinsa ta hanyar bin umarninsa da guje wa haninsa, su kuma riƙa magana wadda take kan hanya ta gaskiya.
Ya tabbatar musu cewa idan sun yi haka, to zai gyara musu ayyukansu ya karɓe su kuma ya ba su lada, ya kuma gafarta musu zunubansu ya yafe musu. Ya bayyana cewa duk wanda ya bi Allah da Manzonsa (ﷺ) to ya sami babban rabo da babu wanda ya fi shi, domin zai sami gidan Aljanna da dacewa da yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman sha’anin shari’a da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗora wa ɗan’adam amanar aiki da ita.

2. Girman matsayin ɗan’adam a tsakanin sauran halittun Allah.

3. Duk ɗan’adam mai siffantuwa ne da siffar zalunci da siffar jahilci. Gwargwadon yadda zai sami imani a zuciyarsa ya riƙa halarto da girman mahaliccinsa, gwargwadon yadda zai nisanci zalunci. Hakanan gwargwadon yadda zai sami ilimin sanin Allah da haƙƙoƙinsa da abin da ya wajaba a kansa na imani da bautar Allah, gwargwadon yadda zai nisanci zalunci.

Suratul Ahzab (72-73)

إِنَّا عَرَضۡنَا ٱلۡأَمَانَةَ عَلَى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَٱلۡجِبَالِ فَأَبَيۡنَ أَن يَحۡمِلۡنَهَا وَأَشۡفَقۡنَ مِنۡهَا وَحَمَلَهَا ٱلۡإِنسَٰنُۖ إِنَّهُۥ كَانَ ظَلُومٗا جَهُولٗا ٧٢ لِّيُعَذِّبَ ٱللَّهُ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ وَٱلۡمُشۡرِكَٰتِ وَيَتُوبَ ٱللَّهُ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٧٣

72. Lalle Mun bijiro da amana ga sammai da ƙasa da duwatsu sai suka ƙi ɗaukar ta suka ji tsoron ta, sai kuwa mutum ya ɗauke ta; lalle shi (mutum) ya kasance mai yawan zalunci ne, mai yawan jahilci.

73. Don Allah Ya azabtar da munafukai maza da munafukai mata, da mushirikai maza da mushirikai mata, Ya kuma karɓi tubar muminai maza da muminai mata. Allah kuwa Ya kasance Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A ayoyin ƙarshe na wannan Sura Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman sha’anin amanar da ya ɗora wa bayinsa wadda ita ce su bi umarninsa su guje wa haninsa a sarari ko a ɓoye da cewa, ya bijiro da wannan amana ga manya-manyan halittunsa, watau sammai da ƙasa da duwatsu, ya ba su zaɓi su ɗauka ko su bari, idan sun ɗauka sun kiyaye ta to suna da kyakkyawan sakamako a wurinsa, idan kuwa sun kasa kiyaye ta to za su haɗu da uƙubarsa, sai suka ƙi yarda su ɗauki wannan amana, suka ji tsoron kada su kasa sauke nauyinta bayan sun ɗauka. Sai kuma Allah ya bijiro da ita amanar ga mutum bisa wancan sharaɗi sai ko ya ɗauke ta. Allah ya bayyana cewa lalle mutum ya tabbata mai yawan zalunci ne ga kansa, mai yawan jahiltar abin da zai kai ya komo.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa mutane sun kasu kashi uku dangane da wannan amanar:
Kashi na farko, su ne munafukai waɗanda a fili suna nuna suna kula da wannan amanar, suna kiyaye ta, amma a zukatansu ba haka ne ba.
Kashi na biyu, su ne mushirikai waɗanda suka yi watsi da amanar a fili da ɓoye.
Kashi na uku, su ne muminai waɗanda suka kiyaye wannan amanar, suka ba da haƙƙoƙinta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa zai azabtar da munafukai mazansu da matansu, da mushirikai mazansu da matansu, saboda munafuncinsu da shirkarsu, sannan kuma zai karɓi tuban muminai mazansu da matansu, domin sun kiyaye amanar da suka ɗauka, sun yi aiki da umarnin Allah sun guji haninsa. Allah ya kasance mai gafara ne ga zunuban bayinsa idan suka tuba, kuma mai rahama ne gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar wa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cikakken yabo da godiya, saboda cikar ikonsa a kan halittunsa.

2. Gamammen ilimin Allah da ya kewaye komai.

3. Tabbatar da sunayen Allah mai gafara mai rahama



34-Suratu Saba'i

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da sunan '*Suratu Saba'i*' saboda a cikinta aka ba da labarin mutanen garin Saba'u na ƙasar Yaman.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Wannan Sura ce *Makkiyya* kamar yadda yake a wurin ɗaukacin malaman tafsiri.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta hamsin da takwas (58) a jerin gwanon saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan *'Suratu Lukman*' gabanin '*Suratuz Zumar'*.

4. Adadin ayoyinta:
Adadin ayoyinta a wurin yawancin malamai hamsin da huɗu ne (54), amma a wurin mutanen Sham hamsin da biyar ne (55).

5. Babban Jigonta:
Bayanin ayoyin Allah cikin halittunsa da jan hankali game da ni'imominsa ga bayinsa da nuna musu cikar Kudurarsa wajen canja yanayi zuwa wani yanayi sakamakon godiyar bayi ko rashin godiyarsu gare shi.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Rushe aƙidun shirka da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Tabbatar da tashi bayan mutuwa.
• Tabbatar da yalwar ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Tabbatar da gaskiyar abin da Manzon Allah (ﷺ) ya ba da labarinsa da abin da Alƙur'ani ya zo da shi.
• Gargaɗin mushirikai da tsoratar da su game da abin da ya auka wa al'ummun da suka gabace su saboda ƙaryatawarsu ga annabawa.
• Ambaton misalin babban tagomashin Allah ga waɗanda suka gode masa a kan ni'imar da ya yi musu, kamar Annabi Dawud da ɗansa Annabi Sulaimanu. Da kuma misalin azabarsa ta duniya da ta lahira ga mutanen da suka butulce masa suka ƙi gode masa a kan ni'imomin da ya yi musu, kamar mutanen Saba'i.
• Gargaɗin mushirikai game da bin Shaiɗan, da kuma mummunan sakamako na wulaƙanci da yake jiran su a ranar alƙiyama idan ba su yi imani ba.
• Albishir da gidan Aljanna ga muminai.

Suratu Saba'i (1-2)
ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَلَهُ ٱلْحَمْدُ فِى ٱلْءَاخِرَةِ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ ۝١ يَعْلَمُ مَا يَلِجُ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا يَخْرُجُ مِنْهَا وَمَا يَنزِلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ وَمَا يَعْرُجُ فِيهَا ۚ وَهُوَ ٱلرَّحِيمُ ٱلْغَفُورُ ۝٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Wanda duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne, kuma godiya ta tabbata a gare Shi a lahira. Shi kuwa Mai hikima ne, Masani.

2. Yana sane da abin da yake shiga cikin ƙasa da abin da yake fitowa daga cikinta, da kuma abin da yake sauka daga sama da abin da yake hawa cikinta. Kuma Shi Mai rahama ne, Mai gafara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da tabbatar wa da kansa yabo da godiya da kirari da siffofin kamala, kuma duk abin da yake cikin sammai da wanda yake ƙasa halittarsa ne kuma mulkinsa ne, shi ne mai gudanar da su. Hakanan shi ne wanda yake da kyakkyawan yabo a lahira, kuma shi mai hikima ne cikin halittarsa da gudanar da al'amuransa, masanin halayen bayinsa ne, babu abin da yake ɓuya a gare shi.

Ya bayyana cewa yana sane da duk abin da yake shiga cikin ƙasa na ruwa da tsirrai, yana kuma sane da duk abin da yake fita daga cikinta na tsirrai da idanuwan ruwa da sauransu. Hakanan yana sane da duk abin da yake sauka daga sama kamar mala'iku da ruwan sama da arziki, yana kuma sane da duk abin da yake hawa sama kamar mala'iku da ayyukan bayinsa da rayukansu. Kuma shi mai rahama ne ga bayinsa muminai, mai gafarta musu zunubansu ne idan sun tuba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karyata ranar alƙiyama kafirci ne.

2. Girman al'amarin ranar alƙiyama wanda har Allah ya umarci Annabi (ﷺ) ya yi rantsuwa a kan tabbatar da ita.

3. Babu wanda ya san lokacin zuwan alƙiyama sai Allah shi kaɗai.

4. Gamewar ilimin Allah ga komai a sammai da ƙasa.

5. Tabbatar da samuwar Lauhul Mahfuzu wanda aka rubuta duk wani abu da zai faru a cikinsa.

6. Halaccin yin rantsuwa idan da buƙatar hakan ko da ba a nemi yin ta ba.

7. Tabbatar da sakamakon ayyuka a ranar alƙiyama gwargwadon aikin kowa.

8. Falalar masu ilimi.

9. Duk abin da wahayi ya zo da shi, Alƙur'ani ko sunnar Annabi (ﷺ) gaskiya ne, duk kuma abin da ya saɓa musu ƙarya ne kuma ɓata ne.

10. Muhimmancin neman ilimin addini, don sanin abin da yake gaskiya da riƙo da shi.

Suratu Saba’i (3-6)

وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَا تَأۡتِينَا ٱلسَّاعَةُۖ قُلۡ بَلَىٰ وَرَبِّي لَتَأۡتِيَنَّكُمۡ عَٰلِمِ ٱلۡغَيۡبِۖ لَا يَعۡزُبُ عَنۡهُ مِثۡقَالُ ذَرَّةٖ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَآ أَصۡغَرُ مِن ذَٰلِكَ وَلَآ أَكۡبَرُ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٣ لِّيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٤ وَٱلَّذِينَ سَعَوۡ فِيٓ ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٞ مِّن رِّجۡزٍ أَلِيمٞ ٥ وَيَرَى ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَ هُوَ ٱلۡحَقَّ وَيَهۡدِيٓ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَمِيدِ ٦

3. Kuma waɗanda suka kafirta suka ce: “Ranar alƙiyama ba za ta zo mana ba.” Ka ce: “A’a, na rantse da Ubangijina, tabbas za ta zo muku, (Allah) Shi ne Masanin gaibu; ba abin da yake ɓoye a gare Shi; daidai da ƙwayar zarra a cikin sammai ko a ƙasa, ko wanda ya fi wannan ƙanƙanta ko ya fi girma, face yana nan (a rubuce) a cikin Lauhul-Mahafuzu.

4. “Don Ya saka wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka kyawawa. Waɗannan suna da gafara da arziki na karamci.”

5. Waɗanda kuwa suka yi ɓarna a cikin ayoyinmu don su nuna gazawarmu, waɗannan suna da mummunar azaba mai raɗaɗi.

6. Waɗanda aka bai wa ilimi kuma suna ganin abin da aka saukar maka daga Ubangijinka shi ne gaskiya, kuma yana shiryarwa ne zuwa hanyar (Allah) Mabuwayi, Sha-yabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana inkarin maganar da kafirai suke faɗa ta cewa alƙiyama ba za ta zo musu ba har abada, don a ganinsu ba gaskiya ce ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tabbatar musu da cewa lalle tabbas sai alƙiyama ta zo musu domin ita gaskiya ce sai dai babu wanda ya san lokacin zuwanta sai Allah shi kaɗai, domin shi ne masanin gaibi, babu abin da yake ɓoye masa daidai da ƙwayar zarra a sammai ko a ƙasa, ko wanda ya fi ta ƙanƙanta ko ya fi ta girma, duk suna rubuce a cikin littafin Lauhul Mahfuzu wanda a cikinsa ne Allah ya rubuta duk abubuwan da za su faru har zuwa tashin alƙiyama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk abubuwan da aka bayyana a cikin wannan littafi masu tabbata ne, domin ya saka wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari da kyakkyawan sakamako. Masu irin wannan siffa kuma suna da gafara daga Allah, ba zai kama su da zunubansu ba, suna da kuma wani arziki na karamci, watau gidan Aljanna. Amma waɗanda suka yi ta ƙoƙarin ɓata ayoyin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar, suka riƙa cewa sihiri ne ko bokanci ko waƙa, to waɗannan a ranar alƙiyama suna da mummunar azaba mai raɗaɗi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da shaida a kan cewa malaman sahabbai da malaman ma’abota littafi waɗanda suka yi imani, duka sun ba da shaida kan cewa Alƙur’ani da aka yi wa Manzon Allah wahayinsa gaskiya ne babu wani kokwanto a cikinsa, yana kuma shiryar da mutane ne zuwa ga hanyar Allah mabuwayi wanda babu mai iya ja da shi kuma sha-yabo a duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Izgili ga masu kira zuwa ga Allah ɗabi’a ce ta kafirai a kowane zamani.

2. Rashin ganin cikar Kudurar Allah da kafirai suke yi shi ne ya sanya su ƙaryata tashi bayan mutuwa.

3. A koyaushe maɓarnata ba sa taƙaitawa a kan ƙaryata gaskiya ko shure ta har sai sun haɗa da tuhumar mai faɗar gaskiyar da ɓata masa suna, don kada ya yi tasiri a kan wasu.

4. Wajabcin duba da nazari cikin halittun Allah na sama da na ƙasa, domin ɗaukar izina da ganin manyan dalilai masu nuna Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Wanda ya mayar da al'amarinsa ga Allah ya zama mai ɗa'a gare shi, shi ne yake saurin amfana da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Saba'i (7-9)

وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ هَلۡ نَدُلُّكُمۡ عَلَىٰ رَجُلٖ يُنَبِّئُكُمۡ إِذَا مُزِّقۡتُمۡ كُلَّ مُمَزَّقٍ إِنَّكُمۡ لَفِي خَلۡقٖ جَدِيدٍ ۝٧ أَفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَم بِهِۦ جِنَّةُۢۗ بَلِ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ فِي ٱلۡعَذَابِ وَٱلضَّلَٰلِ ٱلۡبَعِيدِ ۝٨ أَفَلَمۡ يَرَوۡاْ إِلَىٰ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۚ إِن نَّشَأۡ نَخۡسِفۡ بِهِمُ ٱلۡأَرۡضَ أَوۡ نُسۡقِطۡ عَلَيۡهِمۡ كِسَفٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗ لِّكُلِّ عَبۡدٖ مُّنِيبٖ ۝٩

7. Waɗanda suka kafirta suka ce: "Shin ma nuna muku wani mutum da zai ba ku labarin cewa, idan an yayyaga ku yugu-yugu lallai za ku dawo cikin wata halitta sabuwa?

8. "Shin ya yi wa Allah ƙarya ne, ko kuma yana da wani taɓin hankali ne?" Ba haka ba ne, waɗanda ba sa yin imani da lahira suna cikin azaba da ɓata mai nisa.

9. Ba sa dubawa su ga abin da yake gabansu da abin da yake bayansu na sama da ƙasa? In da Mun ga dama sai Mu nutsar da su cikin ƙasa ko kuma Mu rufto musu da wani yanki daga sama. Lalle a game da wannan tabbas akwai aya ga duk wani bawa mai komawa ga Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin izgili da habaici da kafirai masu ƙaryata ranar alƙiyama suke yi wa Manzon Allah (ﷺ), don ya tabbatar musu cewa bayan sun mutu Allah zai sake tashin su ya yi musu hisabi a kan ayyukansu. Sai suka mayar da abin kamar tatsuniya, suka riƙa faɗa wa junansu cewa su zo su ga wani mutum mai ba da labarin cewa idan sun mutu sun rududduge a ƙasa wai za a sake musu sabuwar halitta a dawo musu da ransu; suna ma ganin cewa ko dai ƙarya yake yi wa Allah, ko kuma yana da taɓin hankali ne wanda yake sanya shi yana maganganu irin waɗannan marasa kan gado. Sai aka mayar musu da martani cewa ba haka abin yake ba; su dai waɗanda ba su yi imani da ranar lahira ba an tanadar musu azaba mai tsanani ne a ranar alƙiyama, a nan duniya kuwa da ma suna cikin ɓata ne mai nisa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya janyo hankalinsu a kan su yi duba cikin abin da ke gabansu na halittar ƙasa da abin da yake bayansu na halittar sama waɗanda suke nuna girman Kudurar Allah da cikar ikonsa, domin su fahimci cewa idan ya ga dama sai ya nutsar da su cikin ƙasa, ko kuma ya rufto musu da wani yankin sama a kansu lokaci guda ya hallaka su, sai dai kawai yana saurara musu ne. Lalle da za su nutsu su duba wannan da sun ga cewa akwai ayar Allah tabbatacciya ga duk wani bawa mai mayar da al'amarinsa ga Allah; su gane cewa wanda yake da wannan ikon lalle yana iya tashin su bayan mutuwarsu da rududdugewarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman falalar da Allah ya yi wa Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Daskararrun abubuwa kamar duwatsu da kuma tsuntsaye, duk suna yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tasbihi.

3. Falalar Allah da ni'imarsa ga mutane ta hanyar hore ƙarfe ga ɗan'adam, domin amfaninsa da ƙere-ƙerensa.

4. Koyarwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yadda zai ƙera sulke wanda ɗan'adam ya gaji wannan sana'a daga gare shi har zuwa yanzu. Wannan wata babbar ni'ima ce ga mutane.

5. Yana da kyau ga duk wani mai sana'a ya yi ƙoƙarin kyautata sana'arsa kada ya riƙa ha'inci a cikinta.

6. Wajibi ne ga wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa wata ni'ima ya nuna godiyarsa gare shi ta hanyar yin ayyuka nagari.

7. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa mutum ɗaya daga cikin wani gida ko wata ƙabila wata baiwa, to wannan ni'ima ce ga duk mutanen wannan gidan ko wannan ƙabilar, don haka za su haɗu wajen godiya ga Allah da yin ayyuka na ƙwarai.

Suratu Saba'i (10-11)
*وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا دَاوُۥدَ مِنَّا فَضۡلٗاۖ يَٰجِبَالُ أَوِّبِي مَعَهُۥ وَٱلطَّيۡرَۖ وَأَلَنَّا لَهُ ٱلۡحَدِيدَ ١٠ أَنِ ٱعۡمَلۡ سَٰبِغَٰتٖ وَقَدِّرۡ فِي ٱلسَّرۡدِۖ وَٱعۡمَلُواْ صَٰلِحًاۖ إِنِّي بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ١١

10. Kuma haƙiƙa Mun bai wa Dawuda falala daga gare Mu; cewa: "Ya ku duwatsu ku riƙa amsa tasbihi tare da shi," da kuma tsuntsaye; Muka kuma tausasa masa ƙarfe.

11. (Muka ce da shi): "Ka riƙa yin cikakken silke, kuma ka kintata wajen yin saƙar; kuma (kai Dawuda da iyalinka) ku yi ayyuka nagari; lalle Ni Mai ganin abin da kuke aikatawa ne."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ɗaya daga cikin annabawansa masu mayar da al'amuransu gare shi, watau Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da cewa lalle ya yi masa wata babbar baiwa ta annabci da mulki, ya kuma ba shi murya mai daɗi wadda yake tasbihi yana tsarkake Allah da ita, don haka sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci duwatsu su riƙa amsa tasbihi tare da shi, ya kuma umarci tsuntsaye su ma su riƙa yi tare da shi. Bugu da ƙari kuma Allah ya hore masa baƙin ƙarfe, ya riƙa sarrafa shi kamar laka, ya ƙera abin da ya ga dama na kayan amfani da shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa ya riƙa ƙera cikakkun silikai na yaƙi domin amfanin mayaƙansa, ya kuma riƙa saisaita ƙusoshin da yake kafawa a jikinsu kada su yi ƙanƙanta sosai su ƙi biyan buƙata, kada kuma su yi girma da yawa yadda za su kasa shiga. Sai kuma ya umarce shi da yin kyakkyawan aiki, ya kuma tabbatar masa cewa shi mai ganin abin da bayinsa suke aikatawa ne, zai kuma yi wa kowa sakayya a kan aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan hore wasu ayoyinsa kamar iska ga wasu daga cikin annabawansa su riƙa sarrafa su yadda suka ga dama.

2. Tabbatar da samuwar aljannu waɗanda su halitta ne da Allah ya yi su da wuta, waɗanda kuma mutane ba sa ganin su sai dai su ne suke ganin mutane.

3. Aljannu sukan yi wa wasu mutane ayyuka ko dai ta hanyar da ta dace kamar yadda suka kasance suna yi wa Annabi Sulaimanu ayyuka iri-iri, ko kuma ta hanyar da ta haramta, kamar alaƙarsu da bokaye waɗanda suke yin shirka da su.

4. Za a iya ganin aljannu kamar yadda Annabi Sulaimanu ya riƙa ganin su suna aiki a gabansa.

5. Aljannu su ma suna ƙarƙashin dokokin Allah, idan suka saba masa za a yi musu azaba da wuta duk kuwa da cewa da ita ne aka halicce su.

6. Wajabcin godiya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).7. Karancin masu godiya ga Allah a cikin bayinsa.

Suratu Saba'i (12-13)
وَلِسُلَيۡمَٰنَ ٱلرِّيحَ غُدُوُّهَا شَهۡرٞ وَرَوَاحُهَا شَهۡرٞۖ وَأَسَلۡنَا لَهُۥ عَيۡنَ ٱلۡقِطۡرِۖ وَمِنَ ٱلۡجِنِّ مَن يَعۡمَلُ بَيۡنَ يَدَيۡهِ بِإِذۡنِ رَبِّهِۦۖ وَمَن يَزِغۡ مِنۡهُمۡ عَنۡ أَمۡرِنَا نُذِقۡهُ مِنۡ عَذَابِ ٱلسَّعِيرِ ١٢ يَعۡمَلُونَ لَهُۥ مَا يَشَآءُ مِن مَّحَٰرِيبَ وَتَمَٰثِيلَ وَجِفَانٖ كَٱلۡجَوَابِ وَقُدُورٖ رَّاسِيَٰتٍۚ ٱعۡمَلُوٓاْ ءَالَ دَاوُۥدَ شُكۡرٗاۚ وَقَلِيلٞ مِّنۡ عِبَادِيَ ٱلشَّكُورُ ١٣

12. Kuma (Muka hore wa) Salaimanu iska, tafiyarta ta safe wata guda ce, ta yamma ma kuma wata guda ce; Muka kuma ɓuɓɓugo masa da narkakkiyar tagulla tana gudana. Daga aljannu kuma akwai masu aiki a wajensa da umarnin Ubangijinsa; wanda kuwa ya kauce wa umarninmu daga cikinsu, to za Mu ɗanɗana masa azabar wutar Sa'ira.

13. Suna aikata masa abubuwan da yake bukata na manya-manyan gine-gine da mutum-mutumi da akusa manya-manya kamar tafkuna da kafaffun tukwane. Ya ku iyalin Dawuda, ku yi aikin (ɗa'a) domin godiya. Masu godiya daga bayina kuwa kaɗan ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana baiwar da ya yi wa Annabi Sulaimanu ɗan Dawud ne. Shi ma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi ƙasaitaccen mulki, ya kuma hore masa iska wadda ita ce abin hawansa, wadda takan yi tafiyar wata guda a lokacin safiya, watau rabin yini, ko gwargwadon marece. Sannan kuma ya ɓuɓɓugo masa narkakkiyar tagulla tana gudana a gabansa don ya riƙa sarrafa ta yadda yake so, don ya ƙera abin da ya ga dama da ita. Hakanan kuma Allah ya hore masa aljannu masu yi masa ayyuka daban-daban da biyayya ga umarninsa; duk kuwa daga cikinsu wanda ya tubure ya ƙi yin biyayya to Allah zai ɗanɗana masa azabar wuta mai ƙuna.
Allah ya bayyana cewa su waɗannan aljannu suna yi wa Annabi Sulaimanu manya-manyan gine-gine da wuraren ibada da mutum-mutumai da manya-manyan akusa masu kamar manyan tafkunan ruwa da kafaffun tuƙwane waɗanda ba a motsa su daga inda suke saboda girmansu. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Dawud da iyalansa da yi wa Allah godiya a kan ni'imomin da ya yi musu ta hanyar yin ayyuka nagari ya kuma tabbatar da cewa kaɗan ne daga cikin bayinsa suke gode wa ni'imarsa.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutuwa rigar duk wani mai rai ce komai girman mulkinsa.

2. Dukkan al'amura suna hannun Allah, don haka da mutuwa da rayuwa shi ne yake hukunta su.

3. Ɗan ƙaramin abu wulaƙantacce zai iya zama sanadiyyar faruwar wani babban al’amari, kamar yadda gara ta zama sanadiyyar aljannu su gane mutuwar Annabi Sulaimanu bayan sun ɗau wani lokaci cikin wahala mai tsanani.

4. Aljannu ba su san komai na gaibu ba.

Suratu Saba’i (14)
فَلَمَّا قَضَيۡنَا عَلَيۡهِ ٱلۡمَوۡتَ مَا دَلَّهُمۡ عَلَىٰ مَوۡتِهِۦٓ إِلَّا دَآبَّةُ ٱلۡأَرۡضِ تَأۡكُلُ مِنسَأَتَهُۥۖ فَلَمَّا خَرَّ تَبَيَّنَتِ ٱلۡجِنُّ أَن لَّوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٱلۡغَيۡبَ مَا لَبِثُواْ فِي ٱلۡعَذَابِ ٱلۡمُهِينِ١٤

14. Sannan lokacin da Muka ƙaddara masa mutuwa ba abin ya nuna musu mutuwarsa sai gara da ta riƙa cin sandarsa; to lokacin da ya faɗi sai aljannu suka gane cewa da sun san gaibu da ba su zauna cikin azabar wulaƙanci ba.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da ajalin Annabi Sulaimanu ya cika, ya mutu yana tsaye ya dogara a kan sandarsa, aljannu suna ta ci gaba da ayyukansu a zatonsu yana nan da ransa yana sa ido a kan ayyukansu. Babu abin da ya nuna musu mutuwarsa sai gara da ta riƙa cin sandarsa a hankali har sandar ta karye, shi kuma ya faɗi ƙasa, to shi ne suka fahimci ashe da ma can ba ya da rai, a nan ne suka dinga cizon yatsa suna cewa ina ma da sun san gaibi kamar yadda ake musu zato, ai da ba su zauna tsawon lokaci ba cikin azaba da wahalar aiki wanda Annabi Sulaimanu ya saka su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rashin godiya ga ni’imomin Allah yana jawowa a rasa su gaba ɗaya.

2. Wajabcin gode wa Allah a kan ni’imominsa.

3. Abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa mutane ni’ima da shi yana iya juya shi ya zama uƙuba a gare su, kamar yadda ya ni’imta mutanen Saba’u da ruwa mai gudana tsakanin gonakinsu. To da suka butulce wa Allah sai ya kwararo musu shi ya hallaka musu gonakinsu da shi.

Suratu Saba’i (15-17)
لَقَدۡ كَانَ لِسَبَإٖ فِي مَسۡكَنِهِمۡ ءَايَةٞۖ جَنَّتَانِ عَن يَمِينٖ وَشِمَالٖۖ كُلُواْ مِن رِّزۡقِ رَبِّكُمۡ وَٱشۡكُرُواْ لَهُۥۚ بَلۡدَةٞ طَيِّبَةٞ وَرَبٌّ غَفُورٞ١٥ فَأَعۡرَضُواْ فَأَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ سَيۡلَ ٱلۡعَرِمِ وَبَدَّلۡنَٰهُم بِجَنَّتَيۡهِمۡ جَنَّتَيۡنِ ذَوَاتَيۡ أُكُلٍ خَمۡطٖ وَأَثۡلٖ وَشَيۡءٖ مِّن سِدۡرٖ قَلِيلٖ١٦ ذَٰلِكَ جَزَيۡنَٰهُم بِمَا كَفَرُواْۖ وَهَلۡ نُجَٰزِيٓ إِلَّا ٱلۡكَفُورَ١٧

15. Haƙiƙa akwai aya game da gidajen ƙabilar Saba’u (ta ƙasar Yaman); ita ce gonakai guda biyu na lambu a hagu da dama; (aka ce da su): “Ku ci daga arzikin Ubangijinku, kuma ku gode masa. Kasa ce mai daɗin zama da kuma Ubangiji mai gafara.

16. Sai suka bijire, sai Muka aiko musu da ambaliyar madatsar ruwan Arimu, Muka kuma musanya musu gonakin nan nasu biyu da wasu gonakin biyu ma’abota ‘ya’ya masu ɗaci da kuma itacen tsamiya, da wani abu kaɗan na ‘ya’yan magarya.

17. Wannan shi ne Muka saka musu (da shi) saboda kafircinsu; ba kuwa Ma yin sakamako (irin wannan) sai ga mai butulci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin mutanen wani gari waɗanda Allah ya yi musu ni'imomi da dama amma sai suka ƙi gode masa, suka butulce wa ni'imominsa; su ne mutanen Saba'u ta ƙasar Yaman. Allah ya albarkaci wuraren zamansu da maka-makan gonaki guda biyu da suka sanya su a tsakiya, damansu da hagunsu, suna cike da shuke-shuke da kayan marmari iri-iri, ni'ima ta baibaye su ta ko'ina, garinsu ya zama mai daɗin zama, ga kuma Allah mai gafarta zunuban waɗanda suka tuba. Sai aka umarce su da su ci daga arzikin da Allah ya ba su kuma su gode wa ni'imominsa. To amma sai suka bijire wa Allah suka ƙi yin imani da manzanninsa, sai Allah ya yi musu uƙuba, ya canza musu wannan ni'imar da jin daɗin ya kawo musu wani bala'i. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sako musu wata ambaliyar ruwa mai ƙarfi ta hanyar karya madatsar ruwan da suka gina, ruwa ya kwararo ya cinye gonakinsu duk suka lalace, suka dawo suna fitar da wasu 'ya'yan itatuwa masu ɗaci da itacen tsamiya da wata 'yar magarya kaɗan. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya yi musu wannan sakayya ne saboda kafircinsu da bijire wa godiya ga Allah, domin ba wanda ya cancanci irin wannan uƙubar sai mutumin da ya kafirce wa Allah ya butulce wa ni'imominsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samun amintattun hanyoyin tafiye-tafiye tsakanin gari da gari, ko ƙasa da ƙasa, domin kasuwanci ko zirga-zirga, babbar ni'ima ce da yake wajaba a yi wa Allah godiya a kanta.

2. Zaman lafiya babbar ni'ima ce ga mutane.

3. Haɗarin butulce wa Allah da rashin godiya a kan ni'imominsa.

4. Mai haƙurin bin dokokin Allah, mai gode wa ni'imominsa, shi ne yake ɗaukar darussa daga ayoyin Allah.

5. Bayanin falalar haƙuri da godiyar Allah.

Suratu Saba'i (18-19)
وَجَعَلۡنَا بَيۡنَهُمۡ وَبَيۡنَ ٱلۡقُرَى ٱلَّتِي بَٰرَكۡنَا فِيهَا قُرٗى ظَٰهِرَةٗ وَقَدَّرۡنَا فِيهَا ٱلسَّيۡرَۖ سِيرُواْ فِيهَا لَيَالِيَ وَأَيَّامًا ءَامِنِينَ ١٨ فَقَالُواْ رَبَّنَا بَٰعِدۡ بَيۡنَ أَسۡفَارِنَا وَظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ فَجَعَلۡنَٰهُمۡ أَحَادِيثَ وَمَزَّقۡنَٰهُمۡ كُلَّ مُمَزَّقٍۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّكُلِّ صَبَّارٖ شَكُورٖ ١٩

18. Muka kuma sanya wasu alƙaryu mabayyana a tsakaninsu (mutan Saba'u) da alƙaryar da Muka sa albarka a cikinta (wato ƙasar Sham), Muka kuma taƙaita zangon tafiya a tsakaninsu (alƙaryun; Muka ce): "Ku yi tafiya a cikinsu dare da rana cikin aminci."

19. Sai suka ce: "Ya Ubangijinmu, Ka ƙaddara nisa tsakanin zangunan tafiyarmu," suka kuwa zalunci kansu, sai Muka mai da su tarihi, Muka kuma warwatsa su wuri-wuri. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga duk wani mai yin haƙuri, mai yin godiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata ni'imar da ya yi wa mutanen Saba'u bayan ni'imar gonaki, watau ni'imar tafiye-tafiyen kasuwanci cikin zaman lafiya da kwanciyar hankali. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a tsakanin garin Saba'u da ƙasar Sham wadda Allah ya yi wa albarka mai yawa, ya sanya wasu fitattun alƙaryu da matafiya kan iya hango su daga nesa, ya kuma sanya

tazara madaidaiciya a tsakaninsu ta yadda idan matafiyi ya bar alƙarya da safe zuwa Azzahar ya isa ta gabanta, idan da yamma ya fito zai iya kwana a alƙaryar da take gaba da ita, har ya isa ƙasar Sham ba tare da ya yi kayan guzurin ruwa ko abinci ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su yi zirga-zirga a tsakanin waɗannan garuruwa dare da rana cikin aminci, ba tare da tsoron yunwa ko ƙishirwa ko maƙiya ba.
To amma sai suka butulce wa wannan ni'imar suka fifita Allah ya sanya tazara a tafiye-tafiyensu ya kawar da waɗannan alƙaryu daga kan hanyarsu ta zuwa Sham ta yadda za su buƙaci ababen hawa da ɗaukar guzurin abinci da abin sha, don suna ganin suna da wadata da yalwar arziƙi. Sun manta cewa a cikinsu akwai talakawan da hakan zai zama wahala a gare su. Sai suka zalunci kawunansu yayin da suka bijire wa ni'imar Allah, suka ƙi gode masa, suka yi wa talakawan cikinsu hassada, sai Allah ya mayar da su tarihi har mutane suka riƙa ba da labarinsu, Allah ya tarwatsa su suka warwatsu a garuruwa daban-daban har haɗuwa da junansu ta yi musu wahala.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa a game da wannan al'amari da ya faru ga mutanen Saba'u akwai aya abar lura da izina ga duk wani mai haƙuri a kan ɗa'ar Allah, da barin saba masa, mai godiya game da ni'imarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani shi ne yake tsare bawa daga faɗawa cikin tarkon Iblis.

2. Iblis shi ne jagoran duk wani ɓatacce, dukkan ɓatattu mabiyansa ne.

3. Bayanin hikimar Allah game da ba wa Shaiɗan damar ya ɓatar da wasu daga cikin 'yan'adam, watau don tantance waɗanda suka yi imani da ranar lahira da waɗanda ba su yi imani ba.

4. Duk wata shakka a kan abin da ya wajaba a yi imani da shi to wannan kafirci ne.

Suratu Saba'i (20-21)
وَلَقَدۡ صَدَّقَ عَلَيۡهِمۡ إِبۡلِيسُ ظَنَّهُۥ فَٱتَّبَعُوهُ إِلَّا فَرِيقٗا مِّنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٢٠ وَمَا كَانَ لَهُۥ عَلَيۡهِم مِّن سُلۡطَٰنٍ إِلَّا لِنَعۡلَمَ مَن يُؤۡمِنُ بِٱلۡأٓخِرَةِ مِمَّنۡ هُوَ مِنۡهَا فِي شَكّٖۗ وَرَبُّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٍ حَفِيظٞ ٢١

20. Kuma haƙiƙa Iblisu ya tabbatar da zatonsa a kansu gaskiya ne, sai suka bi shi, in ban da wata ƙungiya ta muminai.

21. Shi kuwa ba shi da wani ƙarfi a kansu, sai dai (Mun yi haka ne) don Mu bayyana wanda yake imani da ranar lahira da kuma wanda yake cikin shakka game da ita. Ubangijinka kuwa Mai kiyaye komai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa abin da Iblis ya yi zato game da waɗannan kafirai na cewa zai iya ɓatar da su ya raba su da gaskiya ya tabbata, sai suka bi shi a kan kafirci da saɓon Allah, in ban da wata ƙungiya ta muminai waɗanda suka taɓar da zatonsa a kansu, suka ƙi bin tafarkinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi Iblis ba shi da wani ƙarfi da zai iya tursasa su sai sun bi shi, kawai dai ya ƙawata musu ɓata ne su kuma suka amince suka bi shi, kuma Allah ya huwace wa Iblis wannan damar ce, domin ya bayyana wanda ya yi imani da ranar lahira da sakamakon da ke cikinta da wanda yake shakka a kan zuwanta. Sai kuma Allah ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa shi mai kiyaye duk ayyukan bayinsa ne zai kuma yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani abin bauta ba Allah ba, bai mallaki komai a sammai ko a ƙasa da zai amfanar da mai bauta masa da shi ba, don haka duk mai bautar wanin Allah yana wahalar banza ne kawai.

2. Kore ceto irin wanda mushirikai suke da'awar gumakansu za su yi musu a wurin Allah.

3. Tabbatar da ceto na gaskiya wanda Allah zai yi izini da shi ga wanda ya yarda da shi, domin ya ceci wanda Allah ya ga dama a cece shi.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana magana da sautin da ake ji, sai dai ba irin maganar wani mahaluƙi ba, domin siffofin Allah duka sun sha bamban da na halittunsa.

5. Maganar Allah dukkanta gaskiya ce.

6. Tabbatar da ɗaukakar Allah a kan halittunsa.

7. Tsananin tsoron Allah na mala'iku da ƙasƙantar da kawunansu a gare shi.

Suratu Saba'i (22-23)
قُلِ ٱدۡعُواْ ٱلَّذِينَ زَعَمۡتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ لَا يَمۡلِكُونَ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا لَهُمۡ فِيهِمَا مِن شِرۡكٖ وَمَا لَهُۥ مِنۡهُم مِّن ظَهِيرٖ ٢٢ وَلَا تَنفَعُ ٱلشَّفَٰعَةُ عِندَهُۥٓ إِلَّا لِمَنۡ أَذِنَ لَهُۥۚ حَتَّىٰٓ إِذَا فُزِّعَ عَن قُلُوبِهِمۡ قَالُواْ مَاذَا قَالَ رَبُّكُمۡۖ قَالُواْ ٱلۡحَقَّۖ وَهُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡكَبِيرُ ٢٣

22. Ka ce: "Ku kirawo waɗanda kuka riya (cewa su ne iyayen giji) ba Allah ba;" ba sa mallakar wani abu daidai da ƙwayar zarra a cikin sammai ko a cikin ƙasa, ba kuma su da wata tarayya a cikinsu, ba Shi kuma da wani mataimaki daga cikinsu.

23. Kuma ceto ba ya amfani a wurinsa sai ga wanda Ya yi wa izinin yin sa. Har idan an cire tsoro daga cikin zukatansu, sai su ce: "Me Ubangijinku Ya ce ne?" Suka ce: "Gaskiya Ya faɗa, kuma Shi ne Maɗaukaki, Mai girma."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya faɗa wa mushirikai cewa su kirawo allolinsu waɗanda suke da'awar su ne ababen bauta ba Allah ba, domin su amfanar da su ko su yaye musu wata cuta. Tabbas babu abin da za su iya tsinana musu saboda ba su da mallakin wani abu daidai da ƙwayar zarra a cikin sammai ko a ƙasa wanda yake mallakinsu ne su kaɗai, kuma ba su da wata tarayya da Allah a cikin sammai da ƙasa, shi kuma Allah ba shi da wani mai taimakon sa da yake da wata buƙata a wurinsa domin shi mawadaci ne da Zatinsa.
Allah kuma ya tabbatar musu da cewa babu wani ceto da zai yi amfani a wurin Allah sai ga wanda ya yi wa izini, shi kuma ba zai ba da izini ga kowa ba sai wanda ya yarda da shi kaɗai. Saboda isar mulkinsa ne ma idan ya yi wata magana a sama mala'iku gaba ɗaya sukan buga fukafukansu suna masu rusunawa ga wannan maganar tasa, har sai lokacin da tsoronsa ya fita daga cikin zukatansu, sai su tambayi Jibrilu abin da Ubangijinsu ya ce. Shi kuma sai ya amsa musu da cewa gaskiya ya faɗa kuma shi ne Maɗaukaki da Zatinsa da siffarsa da ikonsa, mai girma wanda komai tilas ya rusuna masa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan Allah ya hukunta wani al'amari a sama sai mala'iku su buga fukafukansu, suna masu rusunawa da miƙa wuya ga

maganarsa, wadda suke jin ƙararta kamar ƙarar saukar sarƙa a kan dutse kamfa, Allah yana isar musu da wannan maganar, to idan an cire tsoro daga zukatansu sai su ce, me Ubangijinku ya faɗa? Sai manyan mala'iku su amsa wa mai tambaya da cewa: "Gaskiya ya faɗa, kuma shi ne Maɗaukaki mai girma." [Bukhari #4701].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin tattaunawa da mushirikai domin tsayar musu da hujja.

2. Kafa wa mushrikai hujja da abin da suke gani yau da gobe, wanda ba za su iya musanta shi ba, mai nuna Kaɗaitakar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai.

3. Tausasa magana ga abokin husuma ko da kuwa ya tabbata a kan ɓata yake da kauce wa danganta masa munanan siffofi ko da kuwa ya siffanta da su. Wannan zai taimaka wajen jawo hankalinsa da sanya shi ya yi tunani a kan hanyar da yake bi.

4. Duk wani ɗan'adam shi ne zai ɗauki alhakin aikin da ya yi, a kan aikinsa ne kuma za a tambaye shi ba aikin wani ba.

5. Hukuncin Allah dukkansa adalci ne babu zalunci a cikinsa.

Suratu Saba'i (24-27)
*قُلۡ مَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ قُلِ ٱللَّهُۖ وَإِنَّآ أَوۡ إِيَّاكُمۡ لَعَلَىٰ هُدًى أَوۡ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٢٤ قُل لَّا تُسۡـَٔلُونَ عَمَّآ أَجۡرَمۡنَا وَلَا نُسۡـَٔلُ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ٢٥ قُلۡ يَجۡمَعُ بَيۡنَنَا رَبُّنَا ثُمَّ يَفۡتَحُ بَيۡنَنَا بِٱلۡحَقِّ وَهُوَ ٱلۡفَتَّاحُ ٱلۡعَلِيمُ ٢٦ قُلۡ أَرُونِيَ ٱلَّذِينَ أَلۡحَقۡتُم بِهِۦ شُرَكَآءَ كَلَّاۚ بَلۡ هُوَ ٱللَّهُ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٢٧

24. Ka ce: "Wane ne yake arzuta ku daga sammai da ƙasa?" Ka ce: "Allah ne; kuma mu ko ku (ɗaya daga cikinmu) lalle yana a kan shiriya ko kuma yana cikin ɓata mabayyani."

25. Ka ce: "Ba za a tambaye ku ba game da laifin da muka yi, mu ma kuma ba za a tambaye mu ba game da abin da kuke aikatawa."

26. Ka ce: "Ubangijinmu zai tattara mu sannan Ya yi hukunci a tsakaninmu da gaskiya, Shi ne kuwa Mai hukunci, Masani."

27. Ka ce: "Ku nuna min waɗanda kuka riskar da su a matsayin abokan tarayya da Shi; ku bar wannan magana! Shi ne Allah Mabuwayi Mai hikima."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tambayi mushirikai masu bautar wasu tare da Allah, su faɗa masa wane ne yake arzuta su daga sammai, ya saukar musu da ruwa, ko daga ƙasa ya fito musu da tsirrai da shuke-shukensu? Ba su da wata amsa face su yarda cewa Allah ne kaɗai yake yi musu duka waɗannan abubuwa. Idan kuma sun ƙi bayar da amsa, to Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) shi ya faɗa musu cewa Allah ne yake arzuta su. Sannan ya nuna musu cewa lalle ko shi Manzo da muminai da ke tare da shi suna kaɗaita Allah, ko kuma su kafirai masu shirka da Allah, to dole ne ɗaya daga cikinsu yana kan hanyar shiriya ko yana cikin ɓata mabayyani. Babu shakka muminai su ne a kan shiriya, mushirikai kuwa suna kan ɓata mabayyani.

Sannan Allah ya umarce shi ya bayyana musu cewa a ranar alƙiyama ba za a tambayi mushirikai game da laifukan da muminai suka yi ba, su ma muminai ba za a yi musu tambaya a kan abin da kafirai suka kasance suna aikatawa ba. Don haka kowa shi ne zai ɗauki alhakin aikinsa.
Kuma ya faɗa musu cewa komai daɗewa Allah zai tattara su gaba ɗayansu ranar alƙiyama sannan ya yi musu hukunci na adalci, ya bayyana mai gaskiya da marar gaskiya a cikinsu, domin shi ne mai hukunci da adalci kuma masanin abin da yake hukunci da shi.
Sai kuma Allah ya sake umartar Annabi (ﷺ) ya nemi mushirikai su nuna masa waɗanda suka mayar abokan tarayya da Allah waɗanda har suka cancanci su bauta musu ba Allah ba da cewa, ba haka lamarin yake ba, babu wanda ya isa ya zama abokin tarayya da Allah, domin ba shi da kini ko tamka, shi ne kaɗai mabuwayi wanda babu mai iya karawa da shi, kuma mai hikima cikin halittarsa da hukuncinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Muhammadu (ﷺ) Manzon Allah ne zuwa ga dukkan mutanen duniya.

2. Jigon manzancin Manzon Allah (ﷺ) shi ne albishir da gidan Aljanna ga waɗanda suka yi imani, da gargaɗi da wuta ga waɗanda suka kafirce ko suka saɓa wa Allah.

3. Yawancin mutane ba su san hikimar aiko da manzanni ba.

4. Yawa shi kaɗai ba ya nuna gaskiya ko daidai. Ana sanin gaskiya ne da ƙarfin hujja da dalilinta.

5. Zuwan azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da ajiyayyen lokaci kuma babu wanda ya isa ya gaggauto da shi ko ya jinkirta shi.

Suratu Saba'i (28-30)
وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا كَآفَّةٗ لِّلنَّاسِ بَشِيرٗا وَنَذِيرٗا وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٢٨ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٢٩ قُل لَّكُم مِّيعَادُ يَوۡمٖ لَّا تَسۡتَخِرُونَ عَنۡهُ سَاعَةٗ وَلَا تَسۡتَقۡدِمُونَ ٣٠

28. Ba Mu kuma aiko ka ba sai ga mutane baki ɗaya kana mai albishir mai kuma gargaɗi, sai dai kuma yawancin mutane ba sa sanin (hakan).

29. Suna kuma cewa: "Yaushe ne wannan alƙawarin (na ranar alƙiyama) zai zo, idan kun kasance masu gaskiya?"

30. Ka ce: "Kuna da ajiyayyar rana da ba za ku jinkirta ba daga gare ta daidai da sa'a, ba kuma za ku wuce ta ba."
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, ya aiko shi ne fa zuwa ga ɗaukacin mutanen duniya ba Larabawa kaɗai ba.

An karɓo daga Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "An ba ni abubuwa biyar da ba a taɓa ba wa wani annabi ba gabanina; an ba ni nasara ta hanyar jefa tsoro (a zukatan abokan gabata) na tafiyar tsawon wata guda; an kuma sanya mini ƙasa ta zamo masallaci da abin tsarki, duk inda salla ta riski mutum daga cikin al'ummata to ya sallace ta a wurin; an halatta mini dukiyoyin ganima, wadda ba a halatta wa wani gabanina ba; an kuma ba ni ceto; kowane annabi ana aiko shi ne ga mutanensa kaɗai, ni

kuwa an aiko ni ne zuwa ga dukkan mutane." [Bukhari #335 da Muslim #521]. Annabi (ﷺ) yana cewa: "An aiko ni zuwa ga baƙaƙen mutane da jajaye." [Muslim #521].

Allah ya aiko shi ne kuwa domin ya yi wa masu kiyaye dokokinsa albishir da Aljanna, ya gargaɗi kafirai da masu saɓon Allah, ya tsoratar da su wutar Jahannama. Amma duk da haka da yawa daga cikin mutane ba su san haka ba, da a ce sun sani da ba su ƙaryata shi ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mushirikai suna gaggauto da azabar Allah wadda Manzonsa (ﷺ) yake tsoratar da su ita, har suna cewa yaushe ne wa'adin zuwanta zai kasance, idan har muminai masu gaskiya ne a kan abin da suke riya cewa gaskiya ne? Sai ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya mayar musu da martani da cewa wannan ranar tana nan tafe babu makawa, domin akwai ajiyayyen lokaci da aka sanya musu ranar da zai zo, ba za su yi jinkiri na gwargwadon sa'a ɗaya ba, ba kuma za su gabace ta ba. Wannan ranar kuwa ita ce ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Taurin kan kafirai da dogewarsu a kan kafirci.

2. Duk kafirci zalunci ne, don haka kafirai azzalumai ne.

3. Shugabannin ɓata da mabiyansu za su yi baram-baram da junansu a ranar alƙiyama.

4. Dogewar shugabannin ɓata da aiki tuƙuru dare da rana don ganin sun ɓatar da mabiyansu.

5. Nadama ba ta da wani amfani bayan mutum ya ga azaba ƙuru-ƙuru.

6. Adalcin Allah ga kowa ta yadda ba ya kama kowa sai da laifin da ya aikata.

Suratu Saba'i (31-33)
وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَن نُّؤۡمِنَ بِهَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ وَلَا بِٱلَّذِي بَيۡنَ يَدَيۡهِۗ وَلَوۡ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلظَّٰلِمُونَ مَوۡقُوفُونَ عِندَ رَبِّهِمۡ يَرۡجِعُ بَعۡضُهُمۡ إِلَىٰ بَعۡضٍ ٱلۡقَوۡلَ يَقُولُ ٱلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُواْ لِلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُواْ لَوۡلَآ أَنتُمۡ لَكُنَّا مُؤۡمِنِينَ ٣١ قَالَ ٱلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُواْ لِلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُوٓاْ أَنَحۡنُ صَدَدۡنَٰكُمۡ عَنِ ٱلۡهُدَىٰ بَعۡدَ إِذۡ جَآءَكُمۡ بَلۡ كُنتُم مُّجۡرِمِينَ ٣٢ وَقَالَ ٱلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُواْ لِلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُواْ بَلۡ مَكۡرُ ٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ إِذۡ تَأۡمُرُونَنَآ أَن نَّكۡفُرَ بِٱللَّهِ وَنَجۡعَلَ لَهُۥٓ أَندَادٗاۚ وَأَسَرُّواْ ٱلنَّدَامَةَ لَمَّا رَأَوُاْ ٱلۡعَذَابَۚ وَجَعَلۡنَا ٱلۡأَغۡلَٰلَ فِيٓ أَعۡنَاقِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۖ هَلۡ يُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٣٣

31. Kuma kafirai suka ce: "Ba za mu yi imani da wannan Alƙur'ani ba, haka ma da wanda yake gabaninsa (na saukakkun littattafai)." Da kuwa za ka ga lokacin da za a tsai da azzalumai wajen Ubangijinsu suna mayar wa da juna magana, masu rauninsu (mabiya) suna ce wa masu girman kai (watau shugabanninsu): "Ba don ku ba da mun zamanto muminai."

32. Masu girman kan suka ce wa raunanan: "Yanzu mu muka hana ku ku shiriya bayan ta zo muku? Ba haka ba ne, kun dai kasance masu laifi ne."

33. Raunanan kuma suka ce da manyan masu girman kan: "Ba haka ba ne, makircin dare da na rana ne (da kuke ƙulla mana ya hana mu shiriya), yayin da kuke umartar mu da mu kafirce wa Allah, mu kuma sanya masa abokan tarayya." Suka kuma bayyana nadama lokacin da suka ga azaba, kuma Muka sanya ƙuƙumi a

wuyan waɗanda suka kafirta, ba kuwa za a saka musu da komai ba sai da irin abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana aƙidar Tauhidi, watau kaɗaita shi da bauta, da tabbatar da manzancin Annabinsa (ﷺ) da tabbatar da ranar lahira, sai ya bayyana cewa mushirikai sun riƙa cika baki suna cewa, su ba za su taɓa yin imani da Alƙur'ani ba, kuma ba za su yi imani da sauran littattafan da suka gabace shi ba waɗanda Allah ya saukar wa annabawansa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) irin mummunan halin da waɗannan kafiran za su tsinci kawunansu a ciki a ranar da za a tsayar da su a gabansa cikin wulaƙanci da ƙasƙanci domin yi musu hisabi. A nan ne rigima da cacar baki zai kaure tsakanin mabiya da shugabanninsu, inda za su yi ta tuhumar juna da alhakin jefa su cikin irin wannan mawuyacin hali. Mabiyan za su tuhumi shugabanninsu da cewa su ne suka ɓatar da su suka hana su ba da gaskiya da Allah da Manzonsa (ﷺ). Sai su kuma shugabannin su mayar musu da martani da cewa: ta yaya za su tuhume su da cewa sun hana su yin imani? Yaushe ne ma suka shiga tsakaninsu da shiriya? A'a, da man can su manyan masu laifi ne, watau faɗuwa ce ta zo daidai da zama; sun same su lalatattu sai kawai suka ƙara ingiza su cikin lalata.
Sai su mabiyan su sake mayar musu da magana da cewa makircin da suka yi ta ƙullawa dare da rana shi ne ya zama sanadiyyar ɓatansu, yayin da suka riƙa zuga su suna kafirce wa Allah suna bautar wasu ba shi ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a nan ne dukkansu suka nuna nadamarsu game da kafircin da suka yi a duniya yayin da suka ga azaba a fili, suka kuma tabbatar sai an azabta su da ita.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ɓangare na azabar wulaƙanci da za a yi musu a ranar lokacin da za a sanya ƙuƙumai a wuyansu sakamakon mummunan aikinsu na bautar wanin Allah da saɓa masa a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jin daɗi idan ya yi yawa yakan zamo jarraba ga bawa.

2. Yawan dukiya da 'ya'ya ba alama ce ta dacewa da yardar Allah ba.

3. Mumini shi ne zai amfana da dukiyarsa da 'ya'yansa, amma kafiri ba zai amfana da komai daga cikinsu ba.

4. Arziƙi duka na Allah ne, shi ne yake ba wa wanda ya ga dama ya kuma hana wanda ya ga dama.

5. Ciyar da dukiya don Allah yana daɗa haɓaka ta ya kare ta daga lalacewa.

Suratu Saba'i (34-39)
وَمَآ أَرۡسَلۡنَا فِي قَرۡيَةٖ مِّن نَّذِيرٍ إِلَّا قَالَ مُتۡرَفُوهَآ إِنَّا بِمَآ أُرۡسِلۡتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ٣٤ وَقَالُواْ نَحۡنُ أَكۡثَرُ أَمۡوَٰلٗا وَأَوۡلَٰدٗا وَمَا نَحۡنُ بِمُعَذَّبِينَ ٣٥ قُلۡ
إِنَّ رَبِّي يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقۡدِرُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٣٦ وَمَآ أَمۡوَٰلُكُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُكُم بِٱلَّتِي تُقَرِّبُكُمۡ عِندَنَا زُلۡفَىٰٓ إِلَّا
مَنۡ ءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ جَزَآءُ ٱلضِّعۡفِ بِمَا عَمِلُواْ وَهُمۡ فِي ٱلۡغُرُفَٰتِ ءَامِنُونَ ٣٧ وَٱلَّذِينَ يَسۡعَوۡنَ فِيٓ ءَايَٰتِنَا مُعَٰجِزِينَ أُوْلَٰٓئِكَ
فِي ٱلۡعَذَابِ مُحۡضَرُونَ ٣٨ قُلۡ إِنَّ رَبِّي يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦ وَيَقۡدِرُ لَهُۥۚ وَمَآ أَنفَقۡتُم مِّن شَيۡءٖ فَهُوَ يُخۡلِفُهُۥۖ وَهُوَ خَيۡرُ ٱلرَّٰزِقِينَ ٣٩

34. Ba Mu taɓa aiko wani mai gargaɗi cikin wata alƙarya ba sai mawadatan cikinta sun ce: "Mu dai masu kafirce wa abin da aka aiko ku da shi ne."

35. Suka kuma ce: “Mu muka fi kowa yawan dukiya da ‘ya’ya, kuma mu ba waɗanda za a azabtar ba ne.”

36. Ka ce: “Lalle Ubangijina Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, Ya kuma ƙuntata, sai dai kuma yawancin mutane ba su san (haka) ba.”

37. Kuma ba dukiyoyinku da ‘ya’yanku ne za su kusantar da ku gare Mu ba, sai wanda ya yi imani ya kuma yi aiki nagari, to waɗannan suna da sakamako ninkin-baninki saboda abin da suka aikata, suna kuma amintattu cikin benaye.

38. Waɗanda kuwa suke yin ƙoƙari na ɓata ayoyinmu, don su nuna gazawarmu, waɗannan cikin azaba za a halartar da su.

39. Ka ce: “Lalle Ubangijna Yana shimfiɗa arziki ga wanda ya ga dama cikin bayinsa, Yana kuma ƙuntata masa. Kuma duk abin da kuka ciyar (don Allah), to Shi ne zai ba ku madadinsa, Shi ne kuwa Fiyayyen masu arzutawa.”

A waɗannan ayoyi kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana shaida wa Manzonsa (ﷺ) cewa ba shi kaɗai ne manyan gari mawadata suka ƙaryata ba; wannan wata tsohuwar al’ada ce, wadda babu sanda Allah zai aiko da wani mai gargaɗi a cikin wata alƙarya sai manyan garin mawadata sun nuna masa cewa, su ba za su yi imani da shi su bar bautar gumakansu ba, har ma su riƙa cika baki da cewa, su masu yawan dukiya ne da yawan ‘ya’ya, don haka zancen yi musu azaba idan sun ƙi yin imani ƙarya ne, don kuwa su ba waɗanda za a azabtar ba ne sai dai ma a lahira, idan gaskiya ce, Allah ya ƙara karrama su a can ya ba su dukiya da ‘ya’ya kamar yadda ya ba su a nan duniya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya nuna musu cewa yawan dukiya da yawan ‘ya’ya ba shi ne yake nuna girman matsayin wani a wurin Allah ba, domin shi Ubangiji yakan yalwata dukiya ga wanda ya ga dama domin ya jarraba shi ya gani zai yi godiya ko zai butulce. Yakan kuma ƙuntata arziƙi ga wanda ya ga dama, don ya gwada shi ko zai yi haƙuri ko zai bijire masa. Kuma ya tabbatar musu da cewa ita dukiya da ‘ya’ya da suke tinƙaho da su, ba su ne za su kai su ga samun yardar Allah da kusanci da shi ba. Wanda duk ya yi imani da Allah ya yi kyakkyawan aiki, to shi ne wanda dukiyarsa za ta kusantar da shi ga Allah yayin da ya ciyar da ita dominsa. Hakanan su ma ‘ya’ya za su kusantar da shi ga Allah da kyawawan addu’o’insu gare shi. To muminai masu irin wannan siffa su ne suke da lada ninkin-baninkin na kyawawan ayyukansu, suna kuma amintattu a cikin benaye na Aljanna, ba sa tsoron wata azaba ko mutuwa ko yankewar ni’imar da suke ciki.
Sannan Allah ya bayyana sakamakon kafirai masu ƙoƙarin hana mutane yin imani da ayoyin Allah domin cim ma mummunar manufarsu da cewa su ne waɗanda suka yi asara a nan duniya sannan a lahira za a halarto da su wuta domin yi musu azaba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar Manzonsa (ﷺ) da cewa ya faɗa wa mutane cewa, Ubangijinsa Allah shi ne wanda yake yalwata arziƙi ga wanda ya ga dama daga bayinsa, yake kuma ƙuntata arziƙin wanda ya ga dama, don haka su nemi kusanci gare shi ta hanyar ciyar da dukiyarsu don Allah, domin duk abin da suka ciyar domin shi, to shi ne zai ba su madadinsa a nan duniya, a lahira kuma ya yi musu babban sakamako. Shi ne Fiyayyen mai arzutawa, don haka duk mai neman arziƙi to ya nema a wurinsa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Babu wata rana da bayi za su wayi gari a cikinta face sai wasu mala’iku biyu suna saukowa, ɗayansu yana cewa: ‘Ya Allah ka mayar wa da mai ciyar da dukiyarsa madadin abin da ya ciyar.’ Ɗayan kuma yana cewa: ‘Ya Allah ka lalata dukiyar mai rowa.’” [Bukhari #1442 da Muslim #1010].

An karɓo daga Abu Huraira, har ila yau ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah ya ce: “Ka ciyar ya kai ɗan’adam zan ciyar da kai.” [Bukhari #5352 da Muslim #993].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayyana wa mushirikai masu bautar gumaka da sunan mala’iku cewa ba mala’iku suke bauta wa ba; suna bautar shaiɗanun cikin aljannu ne domin su ne suke ingiza su ga wannan aiki.

2. Duk wanda ya bauta wa wani don ya amfane shi ranar alƙiyama to ba zai amfane shi da komai ba sai dai ya nesanta kansa da shi, ya kuma bayyana biyayyarsa ga Allah.

Suratu Saba’i (40-42)
وَيَوْمَ يَحْشُرُهُمْ جَمِيعًا ثُمَّ يَقُولُ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ أَهَٰٓؤُلَآءِ إِيَّاكُمْ كَانُوا۟ يَعْبُدُونَ ﴿٤٠﴾ قَالُوا۟ سُبْحَٰنَكَ أَنتَ وَلِيُّنَا مِن دُونِهِمْ ۖ بَلْ كَانُوا۟ يَعْبُدُونَ ٱلْجِنَّ ۖ أَكْثَرُهُم بِهِم مُّؤْمِنُونَ ﴿٤١﴾ فَٱلْيَوْمَ لَا يَمْلِكُ بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ نَّفْعًا وَلَا ضَرًّا وَنَقُولُ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ ذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلنَّارِ ٱلَّتِى كُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ﴿٤٢﴾

40. Kuma (ka tuna) ranar da zai tattaro su gaba ɗaya sannan Ya ce da mala’iku: “Ashe yanzu ku ne waɗannan suka kasance suna bauta wa?”

41. Suka ce: “Tsarki ya tabbata a gare Ka, Kai ne Majiɓincinmu ba su ba.” Ba haka ba ne, sun kasance suna bauta wa aljannu ne; mafiya yawansu masu yin imani da su ne.

42. (Sai Allah Ya ce): “To yau shashinku ba zai mallaki amfani ga wani sashi ba ko cutarwa,” za kuma Mu ce da waɗanda suka kafirta: “Ku ɗanɗani azabar wutar da kuka kasance kuna ƙaryata ta.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin da masu bautar mala’iku za su tsinci kansu a ciki ranar alƙiyama, lokacin da Allah zai tattara su gaba ɗaya su da mala’ikun domin ya kama su da hujja, sai ya tambayi mala’iku cewa waɗannan mushirikan da gaske ne ku suke bauta wa a duniya? Sai mala’iku su nesanta kawunansu daga waɗannan mushirikai, su tsarkake Allah wanda ba shi da abokin tarayya, su tabbatar masa cewa shi ne majiɓincinsu masoyinsu, kuma babu wata soyayya da ta haɗa tsakaninsu da waɗannan mushirikan, kawai su dai suna bauta wa aljannu ne waɗanda suke nuna musu su mala’iku ne alhalin ƙarya suke, sai su umarce su da bautar su ba Allah ba, don haka yawancinsu sun yi imani ne da aljannu.
Sai kuma a tabbatar musu da cewa a wannan rana babu wani amfani da ababen bautarsu za su iya tsinana musu ko su cutar da su, domin mulki gaba ɗaya a ranar na Allah ne. Sai Allah ya faɗa wa waɗanda suka zalunci kawunansu da yin shirka da saɓon Allah a duniya cewa su ɗanɗani azabar wuta wadda a duniya suke ƙaryatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Makauniyar biyayya ga iyaye tana hana karɓar gaskiya da bin shiriya.

2. Saboda taurin kan kafirai, duk da kasancewar ayoyin da Annabi (ﷺ) yake karanta musu a fili suke babu wani abu da za su kasa fahimta a ciki, amma sai suka kafirce musu, har ma suka tuhumi Manzon Allah da yi wa Allah ƙarya, suka kuma kira Alƙur’ani da sihiri mabayyani.

3. Babbar baiwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Larabawa bayan a da sun kasance al'umma jahilai ba su da wani littafi da suke karantawa ba kuma wani manzo da ya tashi daga cikinsu yana yi musu wa'azi, sun kasance suna rayuwa a duhu, sai Allah ya aiko musu da Manzo daga cikinsu ya kuma saukar musu da littafi da harshen da suke magana da shi. Ashe bai dace ba ko kaɗan su butulce wa Allah su kafirce wa ni'imarsa.

4. Larabawa sun ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) a kan jahilci ba da wata hujja ba daga Allah.

5. Tarin dukiya da yawan 'ya'ya da ƙarfin jiki ba za su amfani wanda ya kafirce wa Allah da komai ba, kuma ba za su kare masa azabarsa ba ta duniya ko ta lahira.

6. Mai hankali shi ne wanda yake ɗaukar darasi da izina daga tarihi.

Suratu Saba'i (43-45)
وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٖ قَالُواْ مَا هَٰذَآ إِلَّا رَجُلٞ يُرِيدُ أَن يَصُدَّكُمۡ عَمَّا كَانَ يَعۡبُدُ ءَابَآؤُكُمۡ وَقَالُواْ مَا هَٰذَآ إِلَّآ إِفۡكٞ مُّفۡتَرٗىۚ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لِلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمۡ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ مُّبِينٞ ٤٣ وَمَآ ءَاتَيۡنَٰهُم مِّن كُتُبٖ يَدۡرُسُونَهَاۖ وَمَآ أَرۡسَلۡنَآ إِلَيۡهِمۡ قَبۡلَكَ مِن نَّذِيرٖ ٤٤ وَكَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ وَمَا بَلَغُواْ مِعۡشَارَ مَآ ءَاتَيۡنَٰهُمۡ فَكَذَّبُواْ رُسُلِيۖ فَكَيۡفَ كَانَ نَكِيرِ ٤٥

43. Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu mabayyana sai su ce: "Wannan ai ba wani ba ne sai wani mutum da yake nufin ya hana ku (bauta wa) abin da iyayenku suka kasance suna bauta wa." Suka kuma ce: "Wannan ai ba wani abu ba ne in ban da ƙarya da aka ƙirƙira." Waɗanda kuma suka kafirta suka ce game da gaskiya yayin da ta zo musu: "Wannan ba wani abu ba ne sai sihiri mabayyani."

44. Kuma ba Mu kawo musu wasu littattafai da suke karantawa ba, kuma ba Mu aiko musu da wani mai gargaɗi ba gabaninka.

45. Kuma waɗanda suka gabace su sun ƙaryata (annabawa; kafiran Makka) kuwa ba su kai ushurin abin da Muka ba su ba, sai ma sun ƙaryata manzannina; to yaya tsawatarwata ta kasance (gare su)?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana laifin da ya kai kafirai shiga wutar Jahannama da cewa, duk sanda ake karanta musu ayoyin Allah bayyanannu da ya saukar wa Manzonsa domin su ji su yi imani da Kaɗaitakar Allah da manzancin Annabi (ﷺ) sai su bijire har ma su shiga tuhumar Annabi (ﷺ) da cewa shi kawai wani mutum ne da ya zo yake ƙoƙarin ya hana su bautar abin da iyayensu suke bautawa, domin shi ya samu shugabanci da ɗaukaka a cikinsu. Suka kuma zarge shi da cewa shi ne yake ƙirƙirar Alƙur'ani yana cewa daga Allah yake, suka kuma siffanta Alƙur'ani da cewa sihiri ne bayyananne, domin yana raba tsakanin mutum da matarsa da ɗa da ubansa. Don haka suna da'awar cewa addinin da suke bi na iyaye da kakanni shi ne gaskiya.
Sai Allah ya mayar musu da martani cewa, ai babu wasu littattafai da ya saukar musu gabanin Alƙur'ani waɗanda suke karantawa suke ganin gaskiyar abin da suke a kai na addini, ko suka ga an bayyana cewa Annabi ne ya ƙirƙiro Alƙur'ani don haka ƙarya ne ba daga Allah yake ba, kuma ba wani manzo da ya aiko musu kafin zuwan Manzon Allah wanda ya riƙa gargaɗin su da azabar Allah, wanda kuma a wajensa suka sami hujjar yin addinin da suke kai, ko suka sami dalilan ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) a cikinsu. A taƙaice dai ba su da wani ilimi na littafi ko na maganar wani manzo da suka dogara da shi sai tatsuniya kawai da molonka.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗe su da su yi hattara kada azabar da ta samu al'ummun farko waɗanda suka ƙaryata annabawansu su ma ta same su, domin kuwa al'ummu kamar Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Luɗu waɗanda Allah ya ba su yawan dukiya da 'ya'ya da ƙarfin halitta wanda mushirikan Makka ba su sami ushirinsu ba, ba su amfana musu komai ba yayin da suka ƙaryata manzanninsu kuma azabar Allah ta afka musu, dukkansu Allah ya hallaka su saboda ƙaryatawarsu. Don haka su duba su ga yadda tsawatarwar Allah da uƙubarsa ta kasance a gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan mutum yana cikin wata ƙungiya ko wata al'umma da ta yi zurfi a cikin ɓata, ta ƙi sauraron duk wani mai yi musu nasiha, to ba zai iya kuɓutar da kansa daga wannan ɓatan ba har sai ya keɓe shi kaɗai, ya samu damar zurfafa tunaninsa tare da tsarkake zuciyarsa ga Allah shi kaɗai, ta haka ne zai kawar da son zuciya ya gane inda gaskiya take don ya bi ta.

2. Halaccin haɗin kai domin gano gaskiya.

3. Bai dace ga mai kira zuwa ga gaskiya ba ya mayar da kiransa wata hanyar tara abin duniya, ko ya ɗora wa mabiyansa haraji, yin haka zai hana a saurari gaskiyar da yake kira zuwa gare ta.

4. Mai kira zuwa ga Allah ko an karɓi kiransa ko ba a karɓa ba, zai samu cikakken ladansa a wurin Allah.

5. Musulunci shi ne addinin gaskiya, duk inda ya bayyana to zai rushe ƙarya da ɓarnar da take wurin, ya zamanto shi ne mai tasiri a kan zukatan jama'a.

6. Da a ce Annabi (ﷺ) ƙarya yake yi wa Allah, yana kuma kan ɓata ne, to da Allah bai ƙyale shi ya yi ta samun nasara iri-iri a kan abokan gabarsa ba, da tuni Allah ya wargaza tafiyarsa. To amma da yake gaskiya ce ya zo da ita sai Allah ya ba shi nasara a kan maƙiyansa cikin ɗan ƙanƙanin lokaci.

7. Duk sanda bawa ya dace da gaskiya cikin lamuransa, to ya danganta hakan ga Allah ba ga ƙoƙarinsa ko dabararsa ba.

8. Alƙur'ani da sunna su ne maɓuɓɓugar shiriya.

Suratu Saba'i (46-50)

۞قُلۡ إِنَّمَآ أَعِظُكُم بِوَٰحِدَةٍۖ أَن تَقُومُواْ لِلَّهِ مَثۡنَىٰ وَفُرَٰدَىٰ ثُمَّ تَتَفَكَّرُواْۚ مَا بِصَاحِبِكُم مِّن جِنَّةٍۚ إِنۡ هُوَ إِلَّا نَذِيرٞ لَّكُم بَيۡنَ يَدَيۡ عَذَابٖ شَدِيدٖ ٤٦ قُلۡ مَا سَأَلۡتُكُم مِّنۡ أَجۡرٖ فَهُوَ لَكُمۡۖ إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٞ ٤٧ قُلۡ إِنَّ رَبِّي يَقۡذِفُ بِٱلۡحَقِّ عَلَّٰمُ ٱلۡغُيُوبِ ٤٨ قُلۡ جَآءَ ٱلۡحَقُّ وَمَا يُبۡدِئُ ٱلۡبَٰطِلُ وَمَا يُعِيدُ ٤٩ قُلۡ إِن ضَلَلۡتُ فَإِنَّمَآ أَضِلُّ عَلَىٰ نَفۡسِيۖ وَإِنِ ٱهۡتَدَيۡتُ فَبِمَا يُوحِيٓ إِلَيَّ رَبِّيٓۚ إِنَّهُۥ سَمِيعٞ قَرِيبٞ ٥٠

46. Ka ce: "Ni dai kawai ina yi muku wa'azi ne da abu ɗaya; cewa ku tsaya don Allah; bibbiyu da kuma ɗai-ɗai, sannan ku yi tunani. Ba wata hauka tare da mutuminku, shi ba wani ne ba, sai mai yi muku gargaɗin azaba mai tsanani da take gabanku."

47. Ka ce: "Abin da na tambaye ku na wani lada to naku ne; ladana yana wajen Allah kawai; kuma Shi Mai shaida ne a kan komai."

48. Ka ce: "Lalle Ubangijina Yana jefo gaskiya (sai ta rushe ƙarya), Masanin gaibu ne."

49. Ka ce: “Gaskiya ta zo ƙarya kuma ba za ta sake faruwa ba, ba kuma za ta dawo ba.”

50. Ka ce: “Idan na ɓata to na ɓata ne a kan kaina; idan kuwa na shiriya to (na shiriya ne) da abin da Ubangijina Yake yi min wahayinsa. Lalle Shi Mai ji ne, Makusanci.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) cewa ya faɗa wa kafirai masu ƙaryata shi suna jifan sa da hauka, ko kuma yana ƙoƙarin biya wa kansa buƙatarsa ne kawai cewa, yana yi musu wa’azi ne da abu ɗaya, watau su tsaya tsakaninsu da Allah; ko mutum bibbiyu ko ɗai-ɗai, kowa ya yi tunani mai zurfi a karan-kansa ya dubi tarihin rayuwar Annabi Muhammadu (ﷺ) da halayen da aka san shi da su na hankali da gaskiya da amana da sanin yakamata, su gane cewa mai waɗannan halaye bai dace da a kira shi mai taɓin hankali ba, su kuma fahimci cewa shi kawai mai yi musu gargaɗi ne game da wata azaba mai raɗaɗi da za ta same su nan gaba idan ba su tuba sun daina shirka da Allah ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Annabi (ﷺ) ya hau kan dutsen Safa sai ya ƙwala kira sai Kuraishawa suka taru a wurinsa, sai suka tambaye shi: “Me ya same ka?” Sai ya ce: “Me kuke gani idan da zan ba ku labarin cewa ga mayaƙa nan suna son su kawo muku hari da sassafe ko da yamma, shin za ku gaskata ni?” Suka ce: “Kwarai, za mu gaskata ka.” Sai ya ce: “To ni mai yi muku gargaɗin wata azaba ce mai tsanani a gaba gare ku.” Sai Abu Lahab ya ce: “Tir da kai! Da ma don wannan ne ka tara mu?” Sai Allah ya saukar da Surar*‘Tabbat Yada Abi Lahabin’*.” [Bukhari #4801].

Allah kuma ya umarce shi da ya tabbatar musu da cewa ba ya buƙatar su biya shi wani lada na kuɗi, ko wani matsayi a kan abin da yake yi musu wa’azi da shi, yake kuma nuna musu na alheri ko sharri. Ko da kuwa a ce ya nemi su ba da wani lada a kan hakan, to wannan nasu ne ba nasa ba, shi sakamakonsa yana wajen Allah shi kaɗai, kuma shi ne shaida a kan komai, ya shaida cewa Manzon Allah ya isar musu da saƙo, kuma yana ganin ayyukan kowa, zai saka wa kowa a kan aikinsa kyakkyawa ko mummuna.
Don haka sai ya umarce shi ya shaida musu cewa gaskiyar da yake karantar da su ita ba shi ne ya ƙirƙire ta ba, Ubangijinsa ne yake yi masa wahayinta don ya rushe ƙarya da ita, shi Allah masanin gaibu ne, babu abin da zai iya ɓuya a gare shi.
Sannan ya umarce shi ya bayyana musu cewa yanzu gaskiya ta riga ta bayyana da hujjoji masu ƙarfi, ƙarya kuwa ta rushe, ba ita ba alamarta.
Kuma idan kafirai sun ci gaba da tuhumarsa da cewa shi ɓatacce ne wai don ya ƙi bin hanyar iyaye da kakanni, to sai Allah ya umarce shi ya faɗa musu cewa idan ma ya ɓata ne to ya ɓata ne don kansa, bai ƙwari kowa ba, kansa ya ƙwara; idan kuwa ya shiryu ne yana bin hanyar gaskiya, to ba shi ne ya shiryar da kansa ba, ya fahimci shiriyar ne daga abin da Allah ya yi masa wahayinsa na Alƙur’ani. Lalle shi Allah mai jin maganganun bayinsa ne, makusanci ne da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin firgici da tsoro da zai mamaye kafirai a lahira bayan sun ga azaba ƙuru-ƙuru.

2. Lahira gidan sakamako ne ba gidan aiki ba, don haka imani da nadama a can ba za su amfani mutum ba.

3. Shakka game da wani rukuni na imani kafirci ne.

Suratu Saba’i (51-54)

وَلَوۡ تَرَىٰٓ إِذۡ فَزِعُواْ فَلَا فَوۡتَ وَأُخِذُواْ مِن مَّكَانٖ قَرِيبٖ ٥١ وَقَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِهِۦ وَأَنَّىٰ لَهُمُ ٱلتَّنَاوُشُ مِن مَّكَانِۢ بَعِيدٖ ٥٢ وَقَدۡ كَفَرُواْ بِهِۦ مِن قَبۡلُۖ وَيَقۡذِفُونَ بِٱلۡغَيۡبِ مِن مَّكَانِۢ بَعِيدٖ ٥٣ وَحِيلَ بَيۡنَهُمۡ وَبَيۡنَ مَا يَشۡتَهُونَ كَمَا فُعِلَ بِأَشۡيَاعِهِم مِّن قَبۡلُۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ فِي شَكّٖ مُّرِيبٖ ٥٤

51. Da kuwa za ka ga sanda (kafirai) za su firgita, (da ganin azaba), sannan ba wata makuɓuta, kuma aka damƙo su daga makusancin wuri.

52. Suka kuma ce: “Mun yi imani da shi,” yaya kuwa za su iya kamo (wannan imani) daga wuri mai nisa (wato duniya)?

53. Alhalin kuma haƙiƙa sun riga sun kafirta da shi a da can, kuma suna jifa (da zato) ta wani wuri mai nisa.

54. Aka kuma kange tsakaninsu da abin da suke sha’awa (na jin daɗin rayuwa ko komawa duniya) kamar yadda aka yi da ire-irensu tun da can. Lalle su sun kasance cikin shakka mai cike da kokwanto.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai za su yi nadama lokacin da ba za ta amfane su ba da cewa, da a ce ya gan su lokacin da za su ga azaba su firgita, kuma babu wurin gudu ko wajen fakewa, a kama su cikin sauƙi ta wuri makusanci, to da lalle ya ga abin mamaki.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yayin da suka ga mummunar makomarsu sannan ne za su shelanta imaninsu, to amma ina, lokacin karɓar imaninsu ya riga ya wuce, domin sun baro shi can a baya, watau duniya wadda ita ce gidan aiki, amma lahira gidan sakamako ne babu sauran wani aiki a cikinta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ta yaya a ranar alƙiyama za a karɓi imaninsu alhalin a can duniya sun kafirce wa Allah, sun riƙa jifan Manzo (ﷺ) da zace-zace iri-iri da shaci-faɗi, wani lokaci su kira shi mai sihiri, wani lokaci su ce masa boka ko su kira shi mawaƙi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa za a haramta musu duk abin da suke nema na jin daɗin rayuwa ko tuba daga kafirci da samun tsira daga azabar wuta ko komawa duniya domin su gyara abin da suka ɓata. Wannan shi ne irin abin da aka yi wa al’ummu irinsu a baya yayin da suka ƙaryata manzanninsu, sai azabar Allah ta zo musu, a lokacin suka riƙa ƙoƙarin su tuba amma ba a karɓi tubansu ba, domin kuwa sun kasance cikin shakka game da gaskiyar abin da manzanninsu suka zo musu da shi na Tauhidi da imani da ranar lahira, shakkar da ta mamaye zukatansu har suka ƙi yarda da komai.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son yabo, don haka ya yabi kansa.

2. Girman Kudurar Allah da faɗin mulkinsa, wanda ya halicci sammai da ƙasa ba tare da ya gani a wurin wani ba.

3. Tabbatar da samuwar mala’iku.

4. Siffofin wasu mala’iku na cewa suna da fukafukai da suke tashi da su su yi yawo a sama, don isar da umarnin Allah.

5. Bambancin halittar mala’iku, wasu masu fukafukai biyu, wasu masu uku, wasu kuma huɗu, wasu ma fiye da haka kamar Mala’ika Jibrilu mai fukafukai ɗari shida.

35-Suratu Faɗir

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
An fi sanin ta da sunan '*Suratu Faɗir*' saboda lafazin '*Faɗir*' da ya zo a farkonta. Amma a cikin *Sahihul Bukhari* da *Jami'ut Tirmizi* da wasu littattafan tafsiri an ambace ta da sunan '*Suratul Mala'ikah*', domin a farkonta ne aka faɗi siffar mala'iku.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* gaba ɗayanta.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba'in da uku (43) a saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratul Furƙan'* gabanin '*Suratu Maryam'*.

4. Adadin ayoyinta:
A lissafin mutanen Madina da Sham adadin ayoyinta arba'in da shida ne (46). Amma a wurin mutanen Kufa adadinsu arba'in da biyar ne (45).

5. Babban Jigonta:
Babban jigonta shi ne tabbatar da Kaɗaitakar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai da tabbatar da gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ) da gaskiyar Alƙur'ani da bayanin kashe-kashen mutane dangane da imani da waɗannan rukunan imanin.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tabbatar da Kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Tabbatar da gaskiyar Manzon Allah (ﷺ).
• Tabbatar da aƙidar tashi bayan mutuwa da ranar lahira.
• Tunatar da mutane ni'imar da Allah ya yi musu ta samar da su da ba su abin da rayuwarsu take da buƙata; da nuna wa mushirikai rashin amfanin bautar wani ba Allah ba.
• Lallashin Annabi (ﷺ) game da cutarwar mutanensa gare shi da tsoratar da su azabar Allah irin wadda ya hallakar da al'ummun da suka gabace su da ita yayin da suka ƙaryata manzanninsu.
• Gargaɗin mutane game da ruɗin Shaiɗan da makircinsa ga ɗan'adam.

Suratu Faɗir (1)

ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ جَاعِلِ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا أُوْلِيٓ أَجۡنِحَةٖ مَّثۡنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَۚ يَزِيدُ فِي ٱلۡخَلۡقِ مَا يَشَآءُۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Dukkan yabo ya tabbata ga Allah, Mahaliccin sammai da ƙasa Mai sanya mala'iku manzanni masu fukafukai bibbiyu da masu uku-uku da kuma masu huɗu-huɗu. Yakan kuma ƙara abin da Ya ga dama ga halittar. Lalle Allah Mai iko ne a kan komai.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da yi wa kansa kirari da yabo, wanda shi ne ya ƙagi halittar sammai da ƙasa ba tare da ya kwaikwayi wani ba. Wannan yana nuna kamalar Kudurarsa da yalwar rahamarsa da girman mulkinsa. Shi ne wanda ya sanya mala'iku su zama manzanni masu zartar da duk wani umarni da ya yi musu. Daga cikinsu akwai masu isar wa annabawa wahayinsa. Ya kuma hore musu ƙarfin isar da amanar da ya ɗora musu; cikinsu akwai masu fukafukai bibbiyu, akwai masu uku-uku, akwai kuma masu huɗu-huɗu, waɗanda da su suke tashi domin zartar da duk wani umarni da zai yi musu. Yana kuma ƙara abin da ya ga dama a halittar tasu, don haka akwai mala'iku masu fukafukai fiye da huɗu, ya kuma ƙara wa wanda ya ga dama kyau ko wata gaɓa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Annabi (ﷺ) ya ga Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana da fukafukai ɗari shida." [Bukhari #3232 da Muslim #174].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk mabuɗan alheri suna hannun Allah; yana gudanar da komai kamar yadda ya shirya ya ga dama.

2. Wajabcin bawa ya ɗamfara zuciyarsa ga Allah, ya nema a wurinsa shi kaɗai.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mabuwayi ne babu mai iya ƙwato abin da ya riƙe na rahama. Mai hikima ne cikin duk abin da ya saki na rahamarsa.

Suratu Faɗir (2)

مَّا يَفۡتَحِ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ مِن رَّحۡمَةٖ فَلَا مُمۡسِكَ لَهَاۖ وَمَا يُمۡسِكۡ فَلَا مُرۡسِلَ لَهُۥ مِنۢ بَعۡدِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٢

2. Abin da Allah Yake yi wa mutane buɗi da shi na rahama ba mai iya riƙe shi; abin da kuma Yake riƙewa ba mai iya sakin sa bayansa. Shi kuma Mabuwayi ne, Mai hikima.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna kaɗaitarsa da siffar bayarwa ko hanawa; duk wata rahama da ya yi wa mutane buɗi da ita to babu mai iya riƙe ta, duk kuma abin da ya riƙe to babu mai iya sako shi, don haka mabuɗan komai suna hannunsa, shi ne mai ba wa mutane arziki da shiriya da lafiya, shi ne kuma mai hanawa. Shi mabuwayi ne da babu mai iya ja da shi, mai hikima cikin dukkan ayyukansa babu mai cin gyaransa.

Abu Sa'id Alkhudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ruwaito cikin addu'ar da Manzon Allah (ﷺ) yake yi a ruku'u yana cewa: "…Ya Allah babu mai hana abin da ka bayar, babu kuma mai bayar da abin da ka hana, mawadaci wadatarsa ba za ta yi masa amfani ba a wurinka." [Muslim #477].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin tunawa da ni'imomin Allah da yin godiya a kansu.

2. Babu mai arzutawa sai Allah shi kaɗai, don haka a wurinsa ake neman arziki.

3. Butulcin kafirai game da ni'imomin da Allah ya yi musu, suka saki hanyarsa suka kama bauta wa waninsa.

4. Lallashin Manzon Allah (ﷺ) ta hanyar tuna masa labarin manzannin da suka gabace shi.

5. Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama lokacin da kowa zai koma ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Faɗir (3-4)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡۚ هَلۡ مِنۡ خَٰلِقٍ غَيۡرُ ٱللَّهِ يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٣ وَإِن يُكَذِّبُوكَ فَقَدۡ كُذِّبَتۡ رُسُلٞ مِّن قَبۡلِكَۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ ٤

3. Ya ku mutane, ku tuna ni'imar Allah a gare ku. Yanzu akwai wani mahalicci ban da Allah wanda zai arzuta ku daga sama da ƙasa? Babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi. To ta yaya ake karkatar da ku?

4. Idan kuwa suka ƙaryata ka to haƙiƙa an ƙaryata wasu manzannin a gabaninka. Zuwa ga Allah ne kaɗai ake mayar da al'amura.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira mutane baki ɗaya da su tuna ni'imar Allah gare su da zukatansu da harasansu da kuma gaɓoɓinsu, su duba su gani shin akwai wani mai ba su arziki daga sama, watau ya saukar musu ruwan sama, ko yake arzuta su daga ƙasa ta hanyar fitar musu da shuke-shuke da kayan marmari iri-iri? Tabbas babu mai yi musu wannan sai Allah, don haka babu wani wanda ya cancanci a bauta masa sai shi kaɗai, to amma duk da haka sai a samu wasu sun kauce wa hanyarsa sun riƙi wasu ababen bauta tare da shi. Wannan abin mamaki ne.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa game da ƙaryata shi da kafirai suke yi, ya sanar da shi cewa ba shi ne farau ba; manzannin da suka gabace shi ma mutanensu sun ƙaryata su, sai suka yi haƙuri Allah kuma ya hallakar da masu ƙaryatawar, ya tserar da manzanninsa da jama'arsu. Makomar al'amura kuma duka zuwa gare shi take, zai yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama.

2. Duk abin da Allah ya yi alƙawarin faruwarsa gaskiya ne kuma sai ya faru ba makawa.

3. Kwaɗaitarwa da zaburarwa a kan tanadin guzuri domin lahira.

4. Gargaɗi ga mutane a kan kada su bari rayuwar duniya ta ruɗe su har su manta da ranar lahira.

5. Tunatar da ɗan’adam gabar da take tsakaninsa da Shaiɗan, don haka kada ya yi sakaci har ya ruɗe shi ya ingiza shi cikin halaka ta har abada.

6. Kwaɗaitar da muminai a kan su ɗauki matakan kare kansu daga sharrin Shaiɗan ta hanyar ambaton Allah da karatun Alƙur’ani da kauce wa saɓon Allah.

Suratu Faɗir (5-6)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞۖ فَلَا تَغُرَّنَّكُمُ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا وَلَا يَغُرَّنَّكُم بِٱللَّهِ ٱلۡغَرُورُ ٥ إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ لَكُمۡ عَدُوّٞ فَٱتَّخِذُوهُ عَدُوًّاۚ إِنَّمَا يَدۡعُواْ حِزۡبَهُۥ لِيَكُونُواْ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلسَّعِيرِ ٦

5. Ya ku mutane, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne, saboda haka kada rayuwar duniya ta ruɗe ku; kada kuma mai ruɗarwa (Shaiɗan) ya ruɗe ku game da Allah.

6. Lalle Shaiɗan maƙiyinku ne, saboda haka sai ku riƙe shi maƙiyi. Lalle yana kiran mutanensa ne don su zama ‘yan wuta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo mutane gaba ɗaya don ya tabbatar musu da zuwan ranar alƙiyama da cewa, wannan ranar da duk abubuwan da za su wakana a cikinta gaskiya ne babu tantama a kan haka, don haka sai su yi mata kyakkyawan tanadi tun daga nan duniya, kada su yarda su bari rayuwar duniya da ƙyale-ƙyalenta da sha’awe-sha’awenta su ruɗe su, kuma kada su kuskura su bari Shaiɗan mai ruɗi ya ruɗe su, ya ɗora su a kan hanyar ƙarya ya ƙawata musu ita, ya sanya son rayuwar duniya a zukatansu har su mance da lahira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tunatar da su tsohuwar ƙiyayyar Shaiɗan gare su tun a kan kakansu Annabi Adam, don haka su ci gaba da ɗaukar sa babban maƙiyi wanda za su yi ta yaƙi da shi ba ƙaƙƙautawa. Allah ya yi musu kashedi game da haɗarin miƙa wa Shaiɗan ragama, domin zai ja mabiyansa ne zuwa ga shiga wutar Jahannama mai tsananin ruruwa a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karkasuwar mutane gida biyu dangane da biyayya ga Shaiɗan ko rashinta da sakamakon kowane kaso daga cikinsu.

2. Bambancin mabiyin Shaiɗan da mabiyin Allah.

3. Yana daga cikin babbar jarraba ga mutum ya riƙa ganin mummunan aiki a matsayin kyakkyawa; tabbas irin wannan yana da wuyar komawa ga gaskiya.

4. Shiriya da ɓata suna hannun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne yake shiryar da wanda ya ga dama da falalarsa, ya kuma ɓatar da wanda ya ga dama domin ya cancanci ɓatan.

Suratu Faɗir (7-8)
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٞۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٞ كَبِيرٞ ٧ أَفَمَن زُيِّنَ لَهُۥ سُوٓءُ عَمَلِهِۦ فَرَءَاهُ حَسَنٗاۖ فَإِنَّ ٱللَّهَ يُضِلُّ مَن يَشَآءُ وَيَهۡدِي مَن يَشَآءُۖ فَلَا تَذۡهَبۡ نَفۡسُكَ عَلَيۡهِمۡ حَسَرَٰتٍۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ بِمَا يَصۡنَعُونَ ٨

7. Waɗanda suka kafirta suna da (sakamakon) azaba mai tsanani; waɗanda kuwa suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to suna da gafara da lada mai girma.

8. Yanzu wanda aka ƙawata wa mummunan aikinsa ya gan shi kyakkyawa (zai yi daidai da wanda Allah Ya shiryar)? To lalle Allah Yana ɓatar da wanda Ya ga dama Ya shiryi wanda Ya ga dama; saboda haka kada ka halakar da kanka don baƙin ciki game da su. Lalle Allah Masanin abin da suke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana makircin Shaiɗan na ɓatar da mabiyansa da jan su zuwa wuta, sai kuma ya bayyana sakamakon waɗanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa (ﷺ) suka zaɓi su bi tafarkin Shaiɗan da cewa suna da wata azaba mai tsanani a lahira. Waɗanda kuma suka yi imani da Allah da Manzonsa (ﷺ) suka kuma yi kyawawan ayyuka suka guje wa abubuwan da aka hana su, to waɗannan suna da gafarar zunubansu da kuma lada mai girma, watau gidan Aljanna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna bambancin da ke tsakanin waɗannan ɓangarori biyu, ya yi tambaya cewa, yanzu yaya za a yi a daidaita wanda Shaiɗan ya ƙawata masa mummunan aikinsa har ya gan shi kyakkyawa da wanda Allah ya shiryar da shi hanyar gaskiya ya riƙe ta da gaske? Tabbas ba za su zama ɗaya ba. Don haka ba za a taɓa haɗa mabiya Shaiɗan waɗanda suka rungumi kafirci da saɓon Allah da mabiya Allah da Manzonsa waɗanda suka rungumi gaskiya ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa, shiriya da ɓata duka daga Allah ne, shi ne yake ɓatar da wanda ya ga dama, yake kuma shiryar da wanda ya ga dama, don haka ya kwantar wa da Manzo (ﷺ) hankalinsa ya nuna masa kada ya hallaka kansa don baƙin cikin ganin kafirai sun ƙi karɓar gaskiya sun zaɓi ɓata, Allah ya tabbatar masa cewa shi masanin duk abin da suke aikatawa ne, zai kuma yi musu sakayya daidai da ayyukansu.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle Allah mai girma da buwaya ya halicci halittarsa a cikin duhu, sannan ya jefa musu wani yanki na haskensa a wannan ranar, to wanda haskensa ya same shi a wannan ranar sai ya shiriya; wanda kuma ya kuskure masa sai ya ɓata.” [Ahmad #6644 da Tirmizi #2642].

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yalwar ni’imar Allah ga bayinsa.

2. Tabbatar da tashi bayan mutuwa.

3. Tabbatar da sababba na faruwar wasu al’amura kamar yadda Allah ya ga dama.

Suratu Faɗir (9)

وَٱللَّهُ ٱلَّذِىٓ أَرۡسَلَ ٱلرِّيَٰحَ فَتُثِيرُ سَحَابٗا فَسُقۡنَٰهُ إِلَىٰ بَلَدٖ مَّيِّتٖ فَأَحۡيَيۡنَا بِهِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَاۚ كَذَٰلِكَ ٱلنُّشُورُ ٩

9. Kuma Allah Shi ne wanda ya aiko da iska sai ta motsa hadari, sai Muka koro shi zuwa ga mataccen gari, sai Muka raya ƙasa da shi bayan mutuwarta. Kamar haka tayar da (matattu) yake.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman Kudurarsa da yalwar rahamarsa ga bayinsa tare da yi musu nuni a kan yiwuwar tashin matattu bayan mutuwarsu da cewa, shi ne wanda yake aiko da iska sai ta motsa hadari, sai kuma Allah ya kora wannan hadarin zuwa mataccen gari wanda babu tsirrai a cikinsa, sai ya rayar da busasshiyar ƙasa da ruwansa, ya fito da shuke-shukenta da ‘ya’yan itatuwanta. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa kafirai cewa, kamar yadda ya raya wannan matacciyar ƙasa da

ruwan sama har tsirranta suka fito, to hakanan zai tashi matattu a ranar alƙiyama ya dawo musu da rayukansu don a yi musu hisabi.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk mai neman ɗaukaka to ya neme ta a wurin Allah. Shi kuma Allah ba ya ba da ɗaukakarsa sai ga muminai masu ayyuka nagari.

2. Duk wata ɗaukaka da mutum zai samu ba ta hanyar ɗa'a ga Allah ba, to ba ɗaukaka ce ba ƙaskanci ne da taɓewa.

3. Allah yana ɗaukaka kyawawan ayyukan bayinsa kamar yadda kyawawan maganganu suke hawa sama wurinsa.

4. Tabbatar da ɗaukakar Allah a sama, ba gauraye yake da halittunsa ba.

5. Duk wani mugun shiri da maƙiya addinin Allah suke yi wa Musulmi da Musulunci ba za su ci nasara ba wajen rushe wannan addini, ko su gusar da Musulmi daga kansa baki ɗaya.

Suratu Faɗir (10)
مَن كَانَ يُرِيدُ ٱلۡعِزَّةَ فَلِلَّهِ ٱلۡعِزَّةُ جَمِيعًاۚ إِلَيۡهِ يَصۡعَدُ ٱلۡكَلِمُ ٱلطَّيِّبُ وَٱلۡعَمَلُ ٱلصَّٰلِحُ يَرۡفَعُهُۥۚ وَٱلَّذِينَ يَمۡكُرُونَ ٱلسَّيِّـَٔاتِ لَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٞۖ وَمَكۡرُ أُوْلَٰٓئِكَ هُوَ يَبُورُ ١٠

10. Wanda ya zamanto yana nufin ɗaukaka, to ɗaukaka gaba ɗayanta ta Allah ce. Daɗaɗan kalmomi zuwa wurinsa suke hawa, kyakkyawan aiki kuwa shi yake ɗaukaka shi. Waɗanda kuwa suke shirya makirci suna da (sakamakon) azaba mai tsanani, kuma makircin waɗannan shi ne yake lalacewa.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa bayinsa hanyar samun ɗaukaka a duniya da lahira da cewa, ɗaukaka gaba ɗayanta tasa ce, don haka duk mai neman ta to ya lizimci ɗa'a ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), domin shi ne mai ba da ita.
Sannan ya ambaci cewa duk wasu kyawawan maganganu kamar Kalmar Shahada da karatun Alƙur'ani da ambaton Allah, to zuwa wurinsa suke hawa, hakanan kuma yana ɗaukaka aiki nagari zuwa gare shi ya yi wa mai shi sakayya ninkin-baninkin.
Sai kuma Allah ya ambaci waɗanda suke son samun ɗaukaka ta hanyar kafirce wa Allah da aikata miyagun ayyuka da shirya mummunan makirci na hallaka Manzon Allah (ﷺ) da cewa, an tanadar musu da matsananciyar azaba, kuma makircinsu ba zai taɓa yin nasara ba sai dai ya lalace.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kewaye komai.

3. Tsawon rai da rashin tsawonsa abu ne a rubuce a wurin Allah.

4. Tabbatar da matakai uku daga cikin matakan Kaddara, su ne: Ilimi da rubutu da halitta ko samarwa.

5. Ni’imomin Allah da ya aje a cikin koguna, kamar ruwan sha mai daɗi da kifaye da lu’u-lu’u da murjani.

6. Ni’imar samuwar jiragen ruwa ga ɗan’adam da yadda suke nuna cikar Kudurar Allah wajen gudanar da su a kan teku ba tare da sun nutse ba.

7. Ni’imar samuwar dare da yini da rana da wata ga rayuwar ɗan’adam.

8. Bautar wanin Allah da kiran sa don neman biyan wata buƙata shirka ne da Allah.

9. Duk wanda ya bauta wa wani ba Allah ba, sai wannan abin bautar nasa ya kafirce wa bautar da ya yi masa a ranar alƙiyama.

Suratu Faɗir (11-14)

وَٱللَّهُ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطۡفَةٖ ثُمَّ جَعَلَكُمۡ أَزۡوَٰجٗاۚ وَمَا تَحۡمِلُ مِنۡ أُنثَىٰ وَلَا تَضَعُ إِلَّا بِعِلۡمِهِۦۚ وَمَا يُعَمَّرُ مِن مُّعَمَّرٖ وَلَا يُنقَصُ مِنۡ عُمُرِهِۦٓ إِلَّا فِي كِتَٰبٍۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ١١ وَمَا يَسۡتَوِي ٱلۡبَحۡرَانِ هَٰذَا عَذۡبٞ فُرَاتٞ سَآئِغٞ شَرَابُهُۥ وَهَٰذَا مِلۡحٌ أُجَاجٞۖ وَمِن كُلّٖ تَأۡكُلُونَ لَحۡمٗا طَرِيّٗا وَتَسۡتَخۡرِجُونَ حِلۡيَةٗ تَلۡبَسُونَهَاۖ وَتَرَى ٱلۡفُلۡكَ فِيهِ مَوَاخِرَ لِتَبۡتَغُواْ مِن فَضۡلِهِۦ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٢ يُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ كُلّٞ يَجۡرِي لِأَجَلٖ مُّسَمّٗىۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡ لَهُ ٱلۡمُلۡكُۚ وَٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمۡلِكُونَ مِن قِطۡمِيرٍ ١٣ إِن تَدۡعُوهُمۡ لَا يَسۡمَعُواْ دُعَآءَكُمۡ وَلَوۡ سَمِعُواْ مَا ٱسۡتَجَابُواْ لَكُمۡۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ يَكۡفُرُونَ بِشِرۡكِكُمۡۚ وَلَا يُنَبِّئُكَ مِثۡلُ خَبِيرٖ ١٤

11. Kuma Allah Ya halicce ku ne daga turɓaya sannan daga maniyyi, sannan kuma Ya mayar da ku maza da mata. Kuma mace ba za ta ɗauki ciki ba, ba kuma za ta haifu ba sai da saninsa. Ba kuma wani mai tsawon rai da za a raya shi, ko kuma wani da za a rage tsawon ransa face yana (rubuce) a cikin Lauhul-Mahafuzu. Wannan kuwa a wurin Allah mai sauƙi ne.

12. Koguna biyu ba za su daidaita ba, wannan na da daɗin gaske da sauƙin haɗiya, wannan kuma mai zartsin gaske ne, daga kowannensu kuma kuna cin nama sabo (ba bushasshe ba), kuna kuma fito da kayan ado (daga gare su) wanda kuke sawa; kuma kana ganin jiragen ruwa suna keta shi (kogin) don ku nemi falalarsa don kuma ku gode (masa).

13. Yana shigar da dare cikin yini, Yana kuma shigar da yini cikin dare, Ya kuma hore rana da wata kowannensu yana tafiya zuwa ga ajali iyakantacce. (Mai yin wannan kuwa) Shi ne Allah Ubangijinku, mulki (kuwa) nasa ne. Waɗanda kuwa kuke bauta wa ba Shi ba, ba su mallaki ko da rigar ƙwallon dabino ba.

14. Idan kuna kiran su, ba sa jin kiranku, ko da ma sun ji, ba za su amsa muku ba; a ranar alƙiyama kuma za su butulce wa shirkarku. Ba kuwa mai ba ka labari kamar cikakken Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci dalilai bakwai na gani a faɗa masu nuna girman Kudurarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai.
Na farko, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya halicci mutane daga turɓaya, lokacin da ya halicci babansu Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sannan ya halicci sauran ‘yan’adam daga maniyyi, sannan ya sanya su maza da mata suka riƙa auratayya a tsakaninsu suna ci gaba da hayayyafa. Wannan wani babban dalili ne mai tabbatar da cikar Kudurar Allah da Ɗayantakarsa.
Na biyu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk abin da mace za ta ɗauki cikinsa da abin da za ta haife yana gudana ne da saninsa; tun farkon ɗaukar cikin har zuwa haihuwarsa yana sane da komai

nasa, shi ne kuma mai kulawa da shi. Wannan cikakken ilimi nasa yana nuna cancantar a bauta masa shi kaɗai a yi imani da shi.
Na uku, Allah ya bayyana cewa duk wanda zai yi tsawon rai ko mai gajeren kwana, rayuwarsa tana gudana ne yadda Allah ya tsara ta ya kuma rubuta ta a cikin littafin Lauhul Mahfuzu, babu wani wanda ya isa ya canja wani abu in ba shi ba, don haka shi kaɗai ya cancanta a bauta wa.

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mazon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda yake son a faranta masa rai a yalwata masa arzikinsa, a kuma jinkirta masa ajalinsa, to ya sadar da zumuncinsa." [Bukhari #2068 da Muslim #2557].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa wannan aiki ne mai sauƙi a wurinsa, domin cikar iliminsa da kamalar Kudurarsa.
Na huɗu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ɗaya daga cikin ayoyinsa ta haɗa koguna guda biyu, ɗaya mai daɗin gaske mai sauƙin kwankwaɗa, ɗayan kuma mai tsananin zartsi wanda ba ya shayuwa, kuma ga su a wuri ɗaya suna gudana, amma ba wanda zai gauraya da wani. Allah kuma ya bayyana cewa waɗannan koguna biyu ba za su taɓa zama daidai ba, amma kuma daga cikin kowannensu ana samun kifaye, ana kuma fito da lu'u-lu'u da murjani waɗanda mutane suke sawa suna yin ado da su. Lalle wannan ma wani babban dalili ne mai nuna girman Kudurar Allah ta yin yadda ya ga dama, don haka shi kaɗai ya cancanta a bauta wa.
Na biyar, ya janyo hankalin ɗan'adam zuwa ga wata babbar Kudurar tasa, watau manyan jiragen ruwa da ya sanya su suna zirga-zirga a cikin ruwa ɗauke da mutane da kaya niƙi-niƙi, amma duk da haka suna keta ruwa suna gudu ba tare da sun nutse ba. Allah ya yi wa 'yan'adam wannan baiwa ne domin su yi tafiye-tafiyensu gari zuwa gari cikin sauƙi don neman arziki da ɗaukan kayan kasuwancinsu, don kuma su gode masa ta hanyar kaɗaita shi da bauta da bin umarninsa da guje wa haninsa.
Na shida, Allah shi ne yake shigar da dare a cikin yini sai ya ƙara tsawo, ya kuma shigar da yini a cikin dare sai shi ma ya ƙara tsawo. Babu wanda ya isa ya yi wannan aikin in ban da shi kaɗai, don haka shi ne ya cancanci a kaɗaita shi da bauta.
Na bakwai, Allah shi ne ya hore rana da wata domin buƙatar ɗan'adam ta rayuwarsa da ta dabbobinsa da shuke-shukensa, dukkansu kuma suna gudu har zuwa wani iyakantaccen lokaci, watau ranar alƙiyama, a sannan ne tafiyarsu za ta dakata haskensu ya disashe. To wane ne zai iya yin wannan aikin in ban da Allah? Ashe shi kaɗai ya cancanta a bauta wa ba tare da yi masa shirka ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa mai waɗannan ayyuka duka shi ne Allah Ubangijin dukkan halittu, mulki kuma nasa ne shi kaɗai. Abubuwan da kafirai suke bauta wa kuma ba su mallaki ko da gwargwadon rigar ƙwallon dabino ba, to amma abin mamaki sun dage da bautar su ba ji ba gani, sun bar Allah mai cikakkiyar Kudura.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da kafirai kasawar ababen bautarsu, kuma bautar da suke yi musu a banza suke yin ta, domin kuwa idan suna kiran su ba sa jin kiran nasu, saboda daskararrun abubuwa ne marasa rai ballantana su ji kiran. Idan kuwa da a ce ma za su ji kiran nasu, to ba za su iya amsa musu ba. Sannan kuma a ranar alƙiyama za su nesanta kansu da bautar da kafiran suka yi musu, domin su ma a ranar ta kansu suke.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shaida wa Annabi (ﷺ) cewa babu wanda zai ba shi labari na gaskiya kamar Allah mai cikakken sanin komai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan mutane mabuƙata ne wurin Allah, domin shi ne ya samar da su, ya shirya musu gaɓoɓi da sassan jiki, ya hore musu cinsu da shansu da suturarsu da lafiyarsu. Shi ne kuma yake kare su daga masifu da duk

wani abin ƙi, ya raba su da wahalhalu. Suna kuma da buƙata a wurinsa wajen ibadarsu da dogaronsu da fatarsu da ƙaunarsu, in ba don ya datar da su ga hakan ba, da ba su iya bauta masa yadda ya kamata ba.

2. Bayanin adalcin Allah ranar alƙiyama.

3. Gargaɗi da wa'azi ba ya amfanar kowa sai masu tsoron Allah masu bin dokokinsa.

4. Dangantaka da zumunta ba za su yi amfani ba a ranar alƙiyama, sai kyakkyawar zuciya da kyawawan ayyuka.

5. Bin umarnin Allah da guje wa haninsa maslaha ce ta bayi, ba ta mahaliccinsu ba.

Suratu Faɗir (15-18)

*يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ أَنتُمُ ٱلۡفُقَرَآءُ إِلَى ٱللَّهِۖ وَٱللَّهُ هُوَ ٱلۡغَنِيُّ ٱلۡحَمِيدُ ١٥ إِن يَشَأۡ يُذۡهِبۡكُمۡ وَيَأۡتِ بِخَلۡقٖ جَدِيدٖ ١٦ وَمَا ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ بِعَزِيزٖ ١٧ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰۚ وَإِن تَدۡعُ مُثۡقَلَةٌ إِلَىٰ حِمۡلِهَا لَا يُحۡمَلۡ مِنۡهُ شَيۡءٞ وَلَوۡ كَانَ ذَا قُرۡبَىٰٓۗ إِنَّمَا تُنذِرُ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُم بِٱلۡغَيۡبِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَۚ وَمَن تَزَكَّىٰ فَإِنَّمَا يَتَزَكَّىٰ لِنَفۡسِهِۦٓۚ وَإِلَى ٱللَّهِ ٱلۡمَصِيرُ ١٨

15. Ya ku mutane, ku ne mabuƙata a wurin Allah; Allah kuma Shi ne Mawadaci, Sha-yabo.

16. Idan Ya ga dama sai Ya tafiyar da ku Ya kawo wata sabuwar halittar.

17. Wannan kuwa ba wani abu ne ba da zai gagari Allah.

18. Kuma wani mai ɗaukar nauyi ba ya ɗaukan laifin wani. Idan kuma wani mai nannauyan zunubi ya yi kira zuwa ɗauke nauyin nasa, ba za a ɗauke masa komai daga nauyin ba, ko da kuwa ɗan'uwa ne makusanci. Kai dai kana mai gargaɗi ne kawai ga waɗanda suke tsoron Ubangijinsu ba tare da ganin Sa ba, suka kuma tsai da salla. Wanda kuwa ya tsarkaka, to ya tsarkaka ne don kansa. Makoma kuma na ga Allah Shi kaɗai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana gajiyawar `yan'adam da buƙatuwarsu a gare shi da kuma cikakkiyar wadatarsa. Watau koyaushe mutane su ne mabuƙata a wurin Allah cikin dukkan al'amuransu, shi kuwa Allah shi ne mai cikakkiyar wadata ba ya da buƙatar komai a wurin kowa. Shi ne sha-yabo a duniya da lahira bisa abin da ya ƙaddara wa bayinsa.
Allah kuma ya sanar da su cikar ƙudurarsa da cewa, da ya ga dama da sai ya hallaka su gaba ɗayansu, ya kawo wasu sababbin halittu waɗanda za su bauta masa shi kaɗai ba tare da yi masa shirka ba. Ya kuma tabbatar musu da cewa wannan ba abu ne mai wahala a wurinsa ba da zai gagare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kamalar adalcinsa a ranar alƙiyama, domin babu wanda zai ɗauki nauyin zunuban wani, kowa shi zai ɗauki nauyin laifinsa, da kuwa wani mai nannauyan zunubi zai kira wani ya ɗauke masa wani abu daga zunubansa, to da bai samu mai yi masa haka ba ko da kuwa ɗan'uwansa ne makusanci, domin lahira ba kamar duniya ce ba inda ɗan'uwa yake taimaka wa ɗan'uwansa ko aboki ya taimaki abokinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa game da bijirewar da kafirai suke yi masa da cewa, waɗanda kawai yake yi wa gargaɗi kuma su amfana da gargaɗin nasa su ne waɗanda suke jin tsoron Ubangijinsu duk da cewa ba sa ganin sa, kuma suke tsayar da salla yadda ya kamata, to su ne gargaɗinsa yake amfana, don haka duk wanda ya tsarkake kansa daga shirka da saɓon Allah, to kansa ya yi wa, domin

shi ne zai amfana da wannan ba wani ba; Allah ma ba ya da buƙatar ɗa'ar kowa, kowa kuma wurinsa zai koma don ya yi wa kowa sakamako gwargwadon aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani shi ne idon mumini wanda da shi yake ganin hanyar shiriya tar ya bi ta, ya kuma ga hanyar ɓata don ya kauce mata. Hakanan haske ne a zuciya, haske ne a fuska, haske ne a gaɓoɓin mumini. Kuma shi ne rayuwar zuciyarsa da ruhinsa da tunaninsa. A ƙarƙashin inuwarsa ne mumini yakan sami hutu, zuciyarsa da tunaninsa su huta.

2. Kafirci makanta ne ga duk mai yin sa; ba zai bar shi ya ga hanyar shiriya ba sai dai ya yi ta fagamniya da ɗimuwa a cikin duhun ɓata. Zuciyar kafiri a koyaushe ƙuna take yi da shakka da kokwanto da rashin sanin inda ya dosa. Kafiri kuma matacce ne mai matacciyar zuciya mai mataccen tunani.

3. Balagar Alƙur'ani da hikimarsa: Yakan yi wa mutane misali da abubuwan da suke gani da idanunsu, ko suke jin su da kunnuwansu ko a jikinsu, domin ya fahimtar da su wasu abubuwa waɗanda ba a riskar su sai ta hanyar ƙwaƙwalwa da tunani.

4. Aikin Manzon Allah (ﷺ) shi ne isar da saƙon Allah, amma shiriya ba a hannunsa take ba, Allah ne yake shiryar da wanda ya ga dama.

5. Babu wata al'umma da aka taɓa yi face sai da Allah ya aika musu da annabi don ya yi musu gargaɗi.

6. Saboda rahamar Allah da luɗufinsa ga bayinsa ne yake riƙa aika musu da manzanni don su shiryar da su hanyar tsira.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai bar manzanninsa hakanan ba sai da ya ba su littattafai waɗanda suke ɗauke da shiriya da haske.

Suratu Faɗir (19-26)
وَمَا يَسْتَوِي ٱلْأَعْمَىٰ وَٱلْبَصِيرُ ﴿١٩﴾ وَلَا ٱلظُّلُمَٰتُ وَلَا ٱلنُّورُ ﴿٢٠﴾ وَلَا ٱلظِّلُّ وَلَا ٱلْحَرُورُ ﴿٢١﴾ وَمَا يَسْتَوِي ٱلْأَحْيَآءُ وَلَا ٱلْأَمْوَٰتُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُسْمِعُ مَن يَشَآءُ ۖ وَمَآ أَنتَ بِمُسْمِعٍ مَّن فِي ٱلْقُبُورِ ﴿٢٢﴾ إِنْ أَنتَ إِلَّا نَذِيرٌ ﴿٢٣﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَٰكَ بِٱلْحَقِّ بَشِيرًا وَنَذِيرًا ۚ وَإِن مِّنْ أُمَّةٍ إِلَّا خَلَا فِيهَا نَذِيرٌ ﴿٢٤﴾ وَإِن يُكَذِّبُوكَ فَقَدْ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ جَآءَتْهُمْ رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ وَبِٱلزُّبُرِ وَبِٱلْكِتَٰبِ ٱلْمُنِيرِ ﴿٢٥﴾ ثُمَّ أَخَذْتُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۖ فَكَيْفَ كَانَ نَكِيرِ ﴿٢٦﴾

19. Makaho da mai gani ba za su yi daidai ba.

20. Da kuma duhu da haske (ba za su yi daidai ba).

21. Da kuma inuwa da zafin (rana) (ba za su yi daidai ba).

22. Kuma rayayyu da matattu ba za su yi daidai ba. Lalle Allah Yana jiyar da wanda Ya ga dama; kai kuma ba mai iya jiyar da waɗanda suke cikin ƙaburbura ne ba.

23. Kai ba kowa ba ne face mai gargaɗi.

24. Lalle Mu Muka aiko ka da gaskiya kana mai albishir mai kuma gargaɗi. Babu kuma wata al'umma da (ta gabata) sai da wani mai gargaɗi ya zo mata.

25. Idan kuwa sun ƙaryata ka, to haƙiƙa waɗanda suka gabace su ma sun ƙaryata, lokacin da manzanninsu suka zo musu da hujjoji da takardu da kuma littattafai masu hasken (shiriya).

26. Sannan Na damƙi waɗanda suka kafirta; to yaya narkona ya kasance?

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana mana rashin daidaituwar abubuwa kishiyoyin juna a wurin Allah da wurin duk wani mai lafiyayyen hankali. Allah ya nuna cewa makaho da mai gani ba za su yi daidai ba; hakanan mumini da kafiri ba za su zama daidai ba. Sannan duhu da haske ba za su yi daidai ba, to hakanan kafirci da imani ba za su zama daidai ba. Inuwa da iska mai zafi kuma ba za su daidaita ba, to hakanan Aljanna da wuta ba za su zama daidai ba. Rayayyu da matattu kuma ba za su yi daidai ba, to hakanan muminai da kafirai ba za su yi daidai ba. Don haka sai mai hankali ya zaɓi abin da ya fi dacewa da shi. Allah kuma ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa shi ne yake jiyar da gargaɗinsa ga wanda ya ga damar shiriyarsa, shi Manzon Allah ba zai iya jiyar da kafirai ba waɗanda suka yi kama da matattun da suke cikin ƙaburburansu; shi kawai mai gargaɗi ne da tsoratarwa game da azabar Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) manufar aiko shi ga mutane, watau domin ya yi albishir ga muminai da sakamakon gidan Aljanna da Allah ya tanadar musu, ya kuma yi gargaɗi ga kafirai game da azabar da ya tanadar musu a lahira. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa babu wata al'umma da ta gabata face sai da manzo mai gargaɗi ya zo mata ya tsayar mata da hujjar Allah. Don haka idan shi Manzo mutanensa sun ƙaryata shi, to ba a kansa aka fara ƙaryata manzanni ba; al'ummun da suka gabata ma sun ƙaryata annabawansu, kamar Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Luɗu, manzanninsu sun zo musu da hujjoji bayyanannu masu nuna gaskiyarsu, sun kuma zo musu da takardu da littattafai masu haska wa duk wanda ya karanta su hanyar shiriya. To amma duk da haka sai suka kafirce wa Allah da manzanninsa sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su, ya kuma nuna wa Manzonsa cewa tsananin narkonsa kenan ga waɗanda suka ƙaryata wani daga cikin annabawansa. Don haka su ma masu ƙaryata shi su shiga taitayinsu don kada abin da ya sami kafiran farko su ma ya same su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman Kudurar Allah.

2. Falalar ilimi da malamai.

3. Sanin Allah da sunayensa da siffofinsa shi ne yake haifar da tsoron Allah a zuciyar bawa.

Suratu Faɗir (27-28)
أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجْنَا بِهِۦ ثَمَرَٰتٍ مُّخْتَلِفًا أَلْوَٰنُهَا ۚ وَمِنَ ٱلْجِبَالِ جُدَدٌۢ بِيضٌ وَحُمْرٌ مُّخْتَلِفٌ أَلْوَٰنُهَا وَغَرَابِيبُ سُودٌ ﴿٢٧﴾
وَمِنَ ٱلنَّاسِ وَٱلدَّوَآبِّ وَٱلْأَنْعَٰمِ مُخْتَلِفٌ أَلْوَٰنُهُۥ كَذَٰلِكَ ۗ إِنَّمَا يَخْشَى ٱللَّهَ مِنْ عِبَادِهِ ٱلْعُلَمَٰٓؤُا۟ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ غَفُورٌ ﴿٢٨﴾

27. Ba ka ganin lalle Allah Ya saukar da ruwa daga sama sai Muka fitar da 'ya'yan itace iri daban-daban da shi? Daga duwatsu kuma (Ya samar da) hanyoyi farare da jajaye masu launi daban-daban da kuma wasu baƙaƙe ƙirin.

28. Daga mutane kuma da dabbobi da kuma dabbobin ni’ima su ma launinsu daban-daban ne kamar waɗancan. Malamai ne kawai suke tsoron Allah daga bayinsa. Lalle Allah Mabuwayi ne Mai gafara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankulan bayinsa zuwa ga lura da la’akari da wasu dalilai masu nuna girman Kudurarsa da Kaɗaitakarsa, inda ya nuna cewa su duba su ga yadda ya saukar da ruwa daga sama wanda da shi ne kuma ya fitar da tsirrai da shuke-shuke masu yanayi da ɗanɗano daban-daban. Hakanan kuma ya halicci hanyoyin duwatsu masu launuka daban-daban, wasu farare wasu jajaye wasu kuma baƙaƙe ƙirin. Haka ma mutane da dabbobi su ma ya halicce su da launuka daban-daban. Duk waɗannan dalilai ne masu nuna girman Kudurar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai, don haka ne ma Allah ya tabbatar da cewa malamai waɗanda suka san Allah da shari’arsa su ne kawai suke jin tsoron sa da girmama shi yadda ya kamata a ga girmansa. Lalle shi Allah mabuwayi ne babu mai rinjayar sa, mai gafara ne ga zunubban bayinsa yayin da suka tuba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar karatun littafin Allah Alƙur’ani.

2. Falalar malamai masana littafin Allah Alƙur’ani.

3. Mafi girman aiki bayan imani shi ne tsai da salla kamar yadda aka yi umarni. Ita ce ja-gaba a cikin ayyukan gangar jiki.

4. Ciyar da dukiya don Allah shi ne mafi girman ayyukan da za a yi da dukiya.

5. Allah ba ya karɓar duk wani aikin da mutum ya yi ba don shi ba.

6. Duk wani kasuwanci da Allah babu tazgaro ko asara a cikinsa.

7. Karamcin Allah ga bayinsa. Don haka idan mutum ya yi kyakkyawan aiki Allah zai ba shi ladansa cikakke sannan ya ƙara masa ninkin-baninkin.

Suratu Faɗir (29-30)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يَتۡلُونَ كِتَٰبَ ٱللَّهِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنفَقُواْ مِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ سِرّٗا وَعَلَانِيَةٗ يَرۡجُونَ تِجَٰرَةٗ لَّن تَبُورَ ٢٩ لِيُوَفِّيَهُمۡ أُجُورَهُمۡ وَيَزِيدَهُم مِّن فَضۡلِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ غَفُورٞ شَكُورٞ ٣٠

29. Lalle waɗanda suke karanta Littafin Allah suka kuma tsai da salla suka kuma ciyar daga abin da Muka arzuta su a ɓoye da sarari, suna burin kasuwancin da ba zai yi tazgaro ba.

30. Domin Ya cika musu ladansu Ya kuma ƙara musu daga falalarsa. Lalle Shi Mai gafara ne, Mai godiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kyakkyawan sakamako da zai yi wa waɗanda suke karanta littafinsa da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ), watau Alƙur’ani, suka kuma yi aiki da shi, sannan suka tsai da salla yadda ya kamata, suka kuma ciyar daga dukiyar da Allah ya arzuta su da ita ta hanyar fitar da zakka ko ba da sadaka da taimako a fili ko a ɓoye, ba kuma don neman wani suna ba, sai don suna burin ƙulla wani kasuwanci ne da Allah wanda babu tazgaro ko asara a cikinsa, domin kuwa Allah ya ba su ladansu

cikakke, ya kuma ƙara musu wani ladan daga falalarsa; lalle kuma Allah mai gafara ne ga zunubansu, mai godiya ne a kan kyawawan ayyukansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk abin da Alƙur'ani ya zo da shi gaskiya ne, duk kuma abin da ya ci karo da shi to wannan ƙarya ne kuma ɓata ne.

2. Littattafan da suka gabaci Alƙur'ani dukkansu suna gaskata shi, domin kuwa sun ba da labarinsa. Shi ma yana gaskata duk abin da suka labarta game da shi kuma ya bayyana hakan yake, don haka sai gaskiyarsu ta bayyana.

3. Allah ne ya fi kowa sanin bayinsa, don haka ya saukar wa kowace al'umma shari'o'in da suka dace da su a zamaninsu, shi ya sa ma ya yi ta aiko da manzanninsa ɗaya bayan ɗaya har ya cikasa su da Annabi Muhammadu (ﷺ) wanda ya zo da shari'ar da ta dace da ɗan'adam a kowane lokaci har zuwa tashin ƙiyama. To saboda zamantowar wannan al'umma sun fi duk al'ummun da suka gabata tsarkin zuciya da nagartar hankali da kyakkyawan tunani sai Allah ya zaɓe su ya kuma zaɓar musu Musulunci ya gadar musu da Alƙur'ani wanda ya shafe hukuncin duk sauran littattafan da suka gabata.

4. Wasu malamai sun ambaci cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara da ambaton mai zaluntar kansa domin kada ya fitar da ƙauna daga rahamar Allah, sannan ya jinkirta wanda ya yi fice cikin ayyukan alheri zuwa ƙarshe, domin kada ya riƙa ji-ji da kansa har ayyukansa su ɓaci.

Wasu malamai kuma sun ce, an fara da ambaton wanda ya zalunci kansa ne saboda ire-irensa su ne za su fi yawa a Aljanna, waɗanda ba su da zunubbai kuma 'yan kaɗan ne.

5. Ayar tana tabbatar da cewa masu saɓon Allah da bai kai kafirci ba, ba za su dawwama a wuta ba, ko sun shiga za a cire su daga ƙarshe a sa su a Aljanna.

6. Ja'afar As-Sadiƙ yana cewa: "Ya fara da masu zalunci don ya ba da labarin cewa babu abin da zai kusantar da bawa gare shi sai karamcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), sannan kuma a gane cewa zaluntar kai ba zai hana samun zaɓi ba. Sannan ya kawo masu tsakaitawa na biyu, domin ya nuna cewa suna nan tsakanin tsoro da kyakkyawan fata. Sannan ya rufe da masu fice cikin ayyukan alheri, don kada wani ya amince wa kansa makarun Ubangiji. Dukkansu kuwa 'yan Aljanna ne." [Al-Bagawi, *Tafsir*, Juzu'i na 3, shafi na 642].

Suratu Faɗir (31-35)

وَٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ هُوَ ٱلۡحَقُّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِعِبَادِهِۦ لَخَبِيرُۢ بَصِيرٞ ٣١ ثُمَّ أَوۡرَثۡنَا ٱلۡكِتَٰبَ ٱلَّذِينَ ٱصۡطَفَيۡنَا مِنۡ عِبَادِنَاۖ فَمِنۡهُمۡ ظَالِمٞ لِّنَفۡسِهِۦ وَمِنۡهُم مُّقۡتَصِدٞ وَمِنۡهُمۡ سَابِقُۢ بِٱلۡخَيۡرَٰتِ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَضۡلُ ٱلۡكَبِيرُ ٣٢ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ يَدۡخُلُونَهَا يُحَلَّوۡنَ فِيهَا مِنۡ أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٖ وَلُؤۡلُؤٗاۖ وَلِبَاسُهُمۡ فِيهَا حَرِيرٞ ٣٣ وَقَالُواْ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِيٓ أَذۡهَبَ عَنَّا ٱلۡحَزَنَۖ إِنَّ رَبَّنَا لَغَفُورٞ شَكُورٌ ٣٤ ٱلَّذِيٓ أَحَلَّنَا دَارَ ٱلۡمُقَامَةِ مِن فَضۡلِهِۦ لَا يَمَسُّنَا فِيهَا نَصَبٞ وَلَا يَمَسُّنَا فِيهَا لُغُوبٞ ٣٥

31. Kuma abin da Muka yiwo maka wahayinsa na Littafi shi ne gaskiya, yana gaskata abin da yake gabaninsa (na littattafai). Lalle Allah game da bayinsa Masani ne, Mai gani.

32. Sannan Muka gadar da Littafin ga waɗanda Muka zaɓa cikin bayinmu; to daga cikinsu akwai mai cutar kansa, akwai kuma mai tsakaitawa a cikinsu, kuma akwai wanda ya yi fintinkau a aikata alheri da izinin Allah. Wannan kuwa shi ne falala mai girma.

33. (Watau) gidajen Aljanna na dawwama da za su shige su, za a yi musu ado a cikinsu na awarwaron zinare da kuma lu'ulu'u; tufafinsu a cikinsu (gidajen Aljanna) alharini ne.

34. Kuma Su ce: "Yabo ya tabbata ga Allah Wanda Ya yaye mana baƙin ciki; lalle Ubangijinmu Mai gafara ne, Mai godiya.

35. "Wanda Ya saukar da mu a gidan dawwama don falalarsa, ba wata wahala da za ta shafe mu a cikinsa, kuma ba wata gajiya da za ta shafe mu a cikinsa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Alƙur'ani wanda ya yi wahayinsa ga Manzonsa (ﷺ) wanda kafirai suke tababa a kansa gaskiya ne ba wata shakka game da shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da shi yana mai gaskata littattafan da suka gabata, domin duk sun ba da labarinsa, yayin da ya sauka yana ƙunshe da abin da suka yi ishara sai gaskiyarsu su ma ta bayyana. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ya san komai game da bayinsa kuma mai ganin duk abin da suke aikatawa ne, don haka shi ne ya fi sanin abin da zai dace da su na maslahar rayuwarsu ta duniya da lahira.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya gadar da wannan Alƙur'ani ga al'ummar Annabi (ﷺ) wadda ya zaɓe ta cikin sauran al'ummu. Sai kuma ya kasa wannan zaɓaɓɓiyar al'umma kashi uku:Kashi na farko, su ne waɗanda suka zalunci kansu ta hanyar aikata laifuffukan da ba su kai kafirci ba, watau barin wani abu da ya wajaba, ko aikata wani abu da aka haramta aikata shi.
Kashi na biyu, su ne tsaka-tsaki, watau waɗanda suka kula da aikata abubuwan da aka wajabta musu, suka guji abubuwan da aka haramta musu, tare da barin wasu ayyuka na mustahabbi da aikata wasu ayyuka na makaruhi.
Kashi na uku, su ne waɗanda suka yi fice wajen aikata ayyukan alheri da izinin Allah da taimakonsa. Su ne waɗanda bayan aikata wajabci ba sa barin mustahabbai kamar nafilfilu na salla da azumi. Sannan bayan sun guje wa haramun, sukan ƙaurace wa makaruhai ma.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan wannan zaɓi da ya yi wa wannan al'umma ya kuma ba ta Alƙur'ani wanda shi me wata babbar falala ce daga Allah da babu irinta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon duk waɗannan kashe-kashe guda uku da cewa dukkansu za su shiga Aljanna inda za su dawwama a cikinta har abada. Za a ni'imta su da ni'imomi iri-iri, daga cikinsu za a yi musu ado da awarwaro na zinari da kuma lu'u-lu'u, sannan tufafin sawarsu na alharini ne mai kauri da shara-shara.
To bayan sun sami shiga gidajensu na Aljanna sun sami ni'imomi daban-daban a cikinta sai su yi wa Allah godiya wanda ya tafiyar musu da duk wata damuwa ta tsoron a kai su wuta. Suka ƙara tabbatarwa cewa lalle Allah mai gafarta zunuban bayinsa ne matuƙar sun tuba, mai godiya ne a gare su bisa kyawawan ayyukansu waɗanda ya karɓa ya ninninka musu ladansu, ya ba su abin da yawan ayyukansu ba za su ba su shi ba.
Suka kuma ƙara da cewa shi ne wanda ya saukar da su gidan Aljanna da falalarsa ba don ƙoƙarinsu ko dabararsu ba, ya kuma yaye musu duk wata wahala ko gajiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirai a wuta a ranar alƙiyama ba za a karɓi ransu ba, sannan ba za a taɓa sassauta musu azaba ba.
2. Duk wanda ya mutu yana kafiri, to ɗan wuta ne komai nagartar halayensa a duniya, domin imani ne kaɗai yake tserar da bawa daga azabar Allah.

3. Kafirai a lahira za su so a dawo da su duniya domin su gyara ayyukansu su yi imani da Allah da manzanninsa.

4. Kafirai a lahira bayan an saka su wuta za su tabbatar da cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu adalci, don haka ne ma za su buƙaci a mayar da su duniya domin su gyara laifinsu.

5. Duk mutumin da Allah ya ba shi tsawon rai amma bai tuba ya daina saɓa wa Allah ba, har ya mutu, to ba shi da sauran wani hanzari a wurin Allah.

Suratu Faɗir (36-37)

وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَهُمۡ نَارُ جَهَنَّمَ لَا يُقۡضَىٰ عَلَيۡهِمۡ فَيَمُوتُواْ وَلَا يُخَفَّفُ عَنۡهُم مِّنۡ عَذَابِهَاۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي كُلَّ كَفُورٖ ٣٦ وَهُمۡ يَصۡطَرِخُونَ فِيهَا رَبَّنَآ أَخۡرِجۡنَا نَعۡمَلۡ صَٰلِحًا غَيۡرَ ٱلَّذِي كُنَّا نَعۡمَلُۚ أَوَ لَمۡ نُعَمِّرۡكُم مَّا يَتَذَكَّرُ فِيهِ مَن تَذَكَّرَ وَجَآءَكُمُ ٱلنَّذِيرُۖ فَذُوقُواْ فَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِن نَّصِيرٍ ٣٧

36. Waɗanda kuwa suka kafirta suna da (sakamakon) wutar Jahannama, ba za a karɓi rayukansu ba balle su mutu, ba kuma za a sauƙaƙa musu wani abu daga azabarta ba. Kamar haka Muke saka wa kowanne kafiri.

37. Su kuwa suna ta kururuwa a cikinta suna cewa: “Ya Ubangijinmu, Ka fitar da mu, za mu yi aiki nagari, ba irin wanda muka kasance muna aikatawa ba.” (Sai a ce da su): “Yanzu ba Mu raya ku ba gwargwadon lokacin da mai wa’azantuwa zai wa’azantu, kuma mai gargaɗi ya zo muku? Sai ku ɗanɗani (azaba), sannan azzalumai ba su da wani mataimaki.”

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci sakamakon waɗanda suka kafirce masa, inda ya nuna cewa suna da wutar Jahannama wadda za su dawwama a cikinta har abada, ba za a sake hukunta musu wata mutuwa ba a cikinta ballantana su mutu su huta, sannan kuma ba za a sassauta musu azabarta ba; za su yi ta ɗanɗanar azaba ne ba ƙaƙƙautawa. Allah ya bayyana cewa kamar irin wannan azaba ce yake saka wa kowane kafiri mai butulce wa ni’imomin Allah.
Sai kuma ya ƙara bayyana mawuyacin halin da ‘yan wuta za su tsinci kansu a ciki, yayin da za su yi ta kuka suna kururuwa saboda tsananin azabar da ake yi musu suna ta roƙon Ubangiji ya fitar da su daga cikinta, ya sake mayar da su duniya domin su yi aiki nagari, ba irin wanda suka zamanto suna yi ba na saɓon Allah. Sai Allah ya mayar musu da martani da cewa, ashe ba ya raya su gwargwadon lokacin da mai son ya wa’azantu zai wa’azantu ba, ya tuba zuwa ga Allah ya aikata ayyuka nagari, kuma ya aika musu manzo wanda ya zo yana gargaɗin su da azabar Allah? To ba su da wata hujja ko wani hanzari da za su gabatar a gaban Allah. Don haka sai a ce su ɗanɗani azabar wuta domin kuwa azzalumai waɗanda suka cuci kawunansu ta hanyar kafirci da saɓon Allah, ba su da wani mai taimakon su ya kuɓutar da su daga azabar Allah, ko ya sanya a sassauta musu azaba.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah ya yanke uzurin mutumin da ya jinkirta rayuwarsa har ya kai shekara sittin.” [Bukhari #6419].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gamewar ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Gargaɗin mutum a kan kada ya yi tsammanin zai iya ɓoye wa Allah wani abu a zuciyarsa; ya yi ƙoƙarin ya gyara zuciyarsa da abin da Allah yake so.

3. Sanin gaibin sammai da ƙasa na Allah ne shi kaɗai.

4. Al'ummu ba su gushe ba suna maye gurbin juna; idan waɗannan sun shuɗe sai waɗancan su maye gurbinsu. Ba don haka ba da ƙasa ta yi wa mutane ƙunci, rayuwa a bayanta ta gagara.

5. Kafircin kafiri ba ya cutar da Allah da komai, sai dai shi kafiri ya cuci kansa ya ja wa kansa hasarar duniya da lahira.

6. Duk sanda kafiri ya ƙara kafircinsa, to ƙiyayyar Allah a gare shi za ta ƙaru, don haka kafirai a wurin Allah wasu sun fi wasu baƙin jini.

Suratu Faɗir (38-39)
إِنَّ ٱللَّهَ عَٰلِمُ غَيۡبِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٣٨ هُوَ ٱلَّذِي جَعَلَكُمۡ خَلَٰٓئِفَ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ فَمَن كَفَرَ فَعَلَيۡهِ كُفۡرُهُۥۗ وَلَا يَزِيدُ ٱلۡكَٰفِرِينَ كُفۡرُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡ إِلَّا مَقۡتٗاۖ وَلَا يَزِيدُ ٱلۡكَٰفِرِينَ كُفۡرُهُمۡ إِلَّا خَسَارٗا ٣٩

38. Lalle Allah Masanin gaibin sammai da ƙasa ne. Lalle Shi Masanin abubuwan da suke cikin zukata ne.

39. Shi ne wanda Ya sanya ku halifofi a bayan ƙasa. Saboda haka wanda ya kafirta sakamakon kafircinsa yana kansa, kuma kafircin kafirai ba zai ƙara musu komai ba a wurin Ubangijinsu sai ƙiyayya; kuma kafircin kafirai ba zai ƙara musu komai ba sai hasara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikakken iliminsa wanda ya kewaye komai da kowa na fili da na ɓoye, domin shi ne masanin gaibin sammai da ƙasa, babu abin da yake ɓuya gare shi, ya kuma san abin da yake cikin zukatan bayinsa mai kyau ko mummuna, don haka yana yi wa kowa sakayya ne da abin da ya cancanta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da bayinsa cewa, shi ne ya sanya sashinsu yake maye gurbin sashi a bayan ƙasa, don ya jarraba su ya ga irin aikin kowa. Don haka duk wanda ya kafirce wa Allah da abin da manzanninsa suka zo da shi, to sakamakon kafircinsa da zunubinsa yana kansa, ba zai cutar da Allah da komai ba, kuma kafircin kafirai ba zai ƙara musu komai ba a wurin Allah sai matsananciyar ƙiyayya, da hasarar kawunansu da iyalansu da ayyukansu da ma mazaunansu na Aljanna, da a ce sun yi imani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mushirikai masu haɗa Allah da wasu a bauta, ba su da wata hujja ta hankali ko ta wahayi mai goyon bayan shirkarsu.

2. Kafirai da masu saɓon Allah sukan yaudari junansu, su ƙawata wa sashinsu abin da suke yi na kafirci ko na saɓon Allah.

3. Girman Kudurar Allah da haƙurinsa da gafararsa ga bayinsa, ba don haka ba da ya umarci sama da ƙasa sun ruguje saboda sanya masa abokan tarayya da wasu suke yi.

Suratu Faɗir (40-41)

قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ شُرَكَآءَكُمُ ٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَرُونِي مَاذَا خَلَقُواْ مِنَ ٱلۡأَرۡضِ أَمۡ لَهُمۡ شِرۡكٞ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ أَمۡ ءَاتَيۡنَٰهُمۡ كِتَٰبٗا فَهُمۡ عَلَىٰ بَيِّنَتٖ مِّنۡهُۚ بَلۡ إِن يَعِدُ ٱلظَّٰلِمُونَ بَعۡضُهُم بَعۡضًا إِلَّا غُرُورًا ٤٠ ۞إِنَّ ٱللَّهَ يُمۡسِكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ أَن تَزُولَاۚ وَلَئِن زَالَتَآ إِنۡ أَمۡسَكَهُمَا مِنۡ أَحَدٖ مِّنۢ بَعۡدِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ كَانَ حَلِيمًا غَفُورٗا ٤١

40. Ka ce: “Ku ba ni labarin abokan tarayyar naku da kuke bauta wa ba Allah ba, ku nuna min abin da suka halitta daga ƙasa, ko kuma suna da wata tarayya ne a cikin (halittar) sammai, ko kuma Mun ba su wani littafi ne, saboda haka suke da wata hujja daga wajensa?” Ba haka ba ne, ba dai abin da azzalumai suke wa juna alƙawari da shi in ban da ruɗi.

41. Lalle Allah ne Yake riƙe da sammai da ƙasa don kada su ruguje. Lallai kuwa idan da za su ruguje, to ba wani mai riƙe su in ba Shi ba. Lalle Shi (Allah) Ya kasance Mai haƙuri ne, Mai gafara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar da dalilan Kaɗaitakarsa da ruguza hujjar mushirikai ta bauta wa wasu ba Allah ba, yayin da ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya ƙalubalanci kafirai da su kawo wani abu ɗaya da allolinsu suka halitta a nan ƙasa, shin sun halicci duwatsunta ne ko ƙoramunta ko dabbobin cikinta? Ko kuma sun yi tarayya ne da Allah wajen halittar sammai? Ko kuma Allah ya ba su wani littafi ne wanda yake ɗauke da hujjar bautar wasu ba Allah ba? Duk waɗannan abubuwa ba ɗaya da ya faru, kafirai dai suna ruɗar junansu da ƙarerayi ne kawai, suna ingiza juna cikin ɓata da bautar wanin Allah. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman Kudurarsa wadda da ita ce yake riƙe sammai da kasa don kada su gushe. Kuma da za a ƙaddara cewa za su gushe ɗin, to da babu wanda zai iya riƙe su ya hana su gushewa in ba shi ba. Sai dai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hukunta su yi ta zama kamar yadda ya halicce su tun farko don bayinsa su ci gaba da rayuwa a bayan ƙasa, suna amfana da ni’imominsa na sama da na ƙasa cikin kwanciyar hankali da nutsuwa, domin kuma su fahimci girman Kudurarsa, zukatansu su cika da girmama shi da gode masa, su kuma gane haƙurinsa da gafararsa waɗanda suka sanya ba ya gaggauto wa masu laifi azabarsa; yana jinkirta musu ne don su tuba su nemi gafararsa ya kuma gafarta musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin kafircin Kuraishawa waɗanda girman kai ya hana su yin imani da Manzon Allah (ﷺ), bayan a da sun yi rantsuwa a kan cewa idan wani manzo Balarabe ya zo musu za su bi shi.

2. Duk wanda ya gina ramin mugunta shi ne zai faɗa cikinsa ko ba-daɗe ko ba-jima.

3. Sunnar Allah tabbatacciya ce ba ta canzawa koyaushe.

Suratu Faɗir (42-43)

وَأَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ لَئِن جَآءَهُمۡ نَذِيرٞ لَّيَكُونُنَّ أَهۡدَىٰ مِنۡ إِحۡدَى ٱلۡأُمَمِۖ فَلَمَّا جَآءَهُمۡ نَذِيرٞ مَّا زَادَهُمۡ إِلَّا نُفُورًا ٤٢ ٱسۡتِكۡبَارٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَكۡرَ ٱلسَّيِّئِۚ وَلَا يَحِيقُ ٱلۡمَكۡرُ ٱلسَّيِّئُ إِلَّا بِأَهۡلِهِۦۚ فَهَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّا سُنَّتَ ٱلۡأَوَّلِينَۚ فَلَن تَجِدَ لِسُنَّتِ ٱللَّهِ تَبۡدِيلٗاۖ وَلَن تَجِدَ لِسُنَّتِ ٱللَّهِ تَحۡوِيلًا ٤٣

42. Suka kuma rantse da Allah iya rantsuwarsu cewa, lallai idan mai gargaɗi ya zo musu, za su zamanto mafiya shiriya daga ɗayan al'ummu; sannan lokacin da mai gargaɗi ya zo musu ba abin da ya ƙara musu sai nisanta (daga shiriya).

43. Don girman kai a bayan ƙasa da kuma makirci mummuna. (Sakamakon) makirci mummuna kuwa ba ya sauka sai a kan masu shi. Ba abin da suke saurare in ban da sunnar da ta sami mutanen farko. Sannan ba za ka taba samun wani canji ba game da sunnar Allah; kuma ba za ka sami wani sauyi ba game da sunnar Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna irin yadda Kuraishawa suka riƙa rantsuwa iya rantsuwarsu cewa, idan Allah ya aiko musu da manzo wanda zai gargaɗe su game da azabar Allah kamar yadda ya aiko wa al'ummun da suka gabace su manzanni, to lalle sai sun fi waɗancan al'ummu shiriya da bin gaskiya. To amma bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da Manzonsa Muhammadu (ﷺ) yana gargaɗin su game da azabar Allah, wannan zuwan nasa bai ƙara musu komai ba sai nisantar gaskiya da ƙara ƙanƙame wa ƙaryar da suke kai, suka saba alƙawarin da suka yi rantsuwa a kansa, ba don komai ba sai don girman kai a bayan ƙasa da yaudarar mutane da ƙarya. Bugu da ƙari kuma suka shiga ƙulla makirce-makircen yadda za su cutar da Manzon Allah (ﷺ), to amma su sani cewa sakamakon wannan mummunan makirci da suke ƙullawa ba zai sauka a kan kowa ba sai a kansu, domin wannan ita ce sunnar Allah a rayuwa, su kuwa babu abin da suke saurare sai gamuwa da sunnar Allah da ta sami kafiran da suka gabace su, watau Allah ya hallaka su kamar yadda ya hallaka al'ummun da suka gabace su. Allah kuwa ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa, babu wani canji a sunnar Allah wanda zai hana azabar Allah ta sauka a kansu, ba kuma zai kautar da wannan azabar ba zuwa ga wasu daban ba su ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa a kan tafiye-tafiye a bayan ƙasa, domin samun wa'azantuwa da kuma darussa na rayuwa.

2. Al'ummun da suka gabata Allah ya hallaka su saboda kafircinsu, duk da cewa sun fi wannan al'umma tsananin ƙarfi da motsa ƙasa, amma wannan bai yi musu amfanin komai ba lokacin da azabar Allah ta zo musu.

3. Haƙurin Allah ga bayinsa da gafararsa, ba don haka ba da ya hallaka duk wani mai motsi a bayan ƙasa saboda yawan zunuban ɗan'adam da kafircinsa.

Suratu Faɗir (44-45)

أَوَ لَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ وَكَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُعۡجِزَهُۥ مِن شَيۡءٖ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ إِنَّهُۥ كَانَ عَلِيمٗا قَدِيرٗا ٤٤ وَلَوۡ يُؤَاخِذُ ٱللَّهُ ٱلنَّاسَ بِمَا كَسَبُواْ مَا تَرَكَ عَلَىٰ ظَهۡرِهَا مِن دَآبَّةٖ وَلَٰكِن يُؤَخِّرُهُمۡ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗىۖ فَإِذَا جَآءَ أَجَلُهُمۡ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِعِبَادِهِۦ بَصِيرَۢا ٤٥

44. Shin ba su yi tafiya ba ne a cikin ƙasa, sai su ga yaya ƙarshen waɗanda suke gabaninsu ya kasance, alhali kuwa sun zamanto ƙarfafa fiye da su? Ba kuwa wani abu da zai gagari Allah a cikin sammai ko a cikin ƙasa. Lalle Shi Ya kasance Masani ne, Mai iko.

45. Idan da Allah Yana (saurin) damƙar mutane saboda laifin da suka aikata, to da bai bar kowane mai rai ba a bayan ƙasa, sai dai kuma Yana saurara musu ne zuwa wani lokaci ƙayyadajje; to idan lokacin nasu ya zo, to lalle Allah Ya kasance Mai ganin bayinsa ne, (zai kuwa saka musu).

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya janyo hankalin kafiran Kuraishawa waɗanda suke tafiye-tafiye na kasuwanci zuwa garuruwan Sham da Iraƙi da Yaman da cewa, ba su ga yadda ƙarshen al'ummun da suka gabace su ya kasance ba bayan sun ƙaryata annabawansu? Ai Allah ya hallaka su baki ɗaya, duk kuwa da cewa sun fi su tsananin ƙarfi, amma ba su gagari Allah ba, domin babu abin da zai gagare shi a sammai ko a ƙasa, kuma lalle shi masanin abin da masu ƙaryata manzanninsu suke aikatawa ne, kuma mai ikon ya hallaka su ne idan ya ga dama babu mai iya hana shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa da zai gaggauto uƙubarsa ga mutane saboda miyagun ayyukansu da yawan laifuffukansu, to da ya hallaka duk wata halitta da ke tafiya a bayan ƙasa, to amma Allah yana saurara musu ne zuwa wani ƙayyadajjen lokaci, watau ranar alƙiyama, idan ta zo ne za su tabbatar da cewa lalle Allah mai ganin bayinsa ne da ayyukansu kuma zai yi musu sakayya a kan dukkan ayyukan da suka gabatar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nuni zuwa ga mu'ujizar Alƙur'ani mai girma.

2. Tabbatar da hikimomin da ke ƙunshe a cikin Alƙur'ani wanda yake sanya komai a mahallainsa da ya dace, kuma hukunce-hukuncen shari'a duka suna ƙunshe da matuƙar hikima da dacewa.

3. Tabbatar da manzancin Annabi (ﷺ) da nuna cewa duk abin da ya zo da shi na rukunan addini daidai suke da abin da sauran annabawa suka zo da shi.

4. Duk abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi hanya ce madaidaiciya. Duk wata hanya karkatacciya to ba hanyar Manzon Allah (ﷺ) ba ce.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko Annabi Muhammadu (ﷺ) ne zuwa ga al'ummar da wani manzo bai zo mata ba.

6. Muminai waɗanda suka miƙa wuya ga Allah, suka kuma bi manzonsa 'yan kaɗan ne a koyaushe. Don haka yawa shi kaɗai ba ma'auni ne na gane gaskiya ko daidai ba.

7. Bijire wa gaskiya da yawan saɓon Allah yakan zame wa bawa ƙuƙumi da shamaki wanda zai hana shi ganin gaskiya ya miƙa wuya gare ta.

8. Waɗanda Allah ya riga ya hukunta taɓewarsu gargaɗi ba ya yi musu tasiri ko kaɗan.

9. Aiki da koyarwar Alƙur'ani da tsoron Allah su ne sababban shiga Aljanna.

10. Falalar ayyukan alheri masu gudana (wato sadaka jariya) bayan mutuwar bawa mumini.

11. Tsoron Allah na gaske shi ne mutum ya tsorace shi a yayin da babu mai ganin sa sai Allah.



36-Suratu Yasin

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna '*Suratu Yasin*', watau da haruffan farko na cikinta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa Sura ce *Makkiyya*kamar yadda Ibni Aɗiyya ya ambata a tafsirinsa.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba'in da ɗaya (41) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratul Jinni'*gabanin '*Suratul Furƙan'*.

4. Adadin ayoyinta:
Adadin ayoyinta tamanin da uku ne (83) a lissafin mutanen Kufa. Amma a lissafin sauran malamai adadinsu tamanin da biyu ne (82).

5. Falalarta:
Babu wani hadisi na Manzon Allah (ﷺ) da ya inganta game da falalarta.

6. Babban Jigonta:
Bayanin ƙarfafan dalilai masu tabbatar da manzanci da kuma tashi bayan mutuwa.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Nuna girman Alƙur'ani da gaskiyarsa da gaskiyar saƙon da ya zo da shi, don ceton al'ummar Larabawa waɗanda ba a aiko musu da wani manzo a baya ba.
• Bayanin siffofin waɗanda suka bijire wa Musulunci suka ƙi amfana da shiriyarsa, saɓanin muminai masu tsoron Allah waɗanda suka bi tafarki madaidaici.
• Kwatanta ɓangaren muminai waɗanda suka gaskata Manzon Allah (ﷺ) da kuma ɓangaren kafirai masu ƙaryata shi, kwatanta su da mutanen alƙarya waɗanda suka ƙaryata manzonsu da bayanin ɓangarorin biyu.
• Ba su misali, har ila yau, da al'ummun da Allah ya hallaka gabaninsu saboda sun ƙaryata annabawansu.
• Nuni zuwa ga manyan dalilai masu tabbatar da tashin alƙiyama.
• Bayanin wasu daga cikin ni'imomin Allah ga bayinsa masu nuna Ɗayantakarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da shirka ba.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) a kan ya ci gaba da haƙuri game da ƙaryatawar da mutanensa suke yi masa, ya kuma lura da cewa su waɗannan masu ƙaryata shi sun ƙaryata Kudurar Allah ma domin suna ganin ba zai iya dawo da su ba bayan sun mutu sun rududduge, tare da cewa suna ganin dalilai da hujjoji masu ƙarfi da suke tabbatar da yiwuwar tashin matacce bayan mutuwarsa.

Suratu Yasin (1-12)

يسٓ ۝١ وَٱلۡقُرۡءَانِ ٱلۡحَكِيمِ ۝٢ إِنَّكَ لَمِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ۝٣ عَلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ۝٤ تَنزِيلَ ٱلۡعَزِيزِ ٱلرَّحِيمِ ۝٥ لِتُنذِرَ قَوۡمٗا مَّآ أُنذِرَ ءَابَآؤُهُمۡ فَهُمۡ غَٰفِلُونَ ۝٦ لَقَدۡ حَقَّ ٱلۡقَوۡلُ عَلَىٰٓ أَكۡثَرِهِمۡ فَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ۝٧ إِنَّا جَعَلۡنَا فِيٓ أَعۡنَٰقِهِمۡ أَغۡلَٰلٗا فَهِيَ إِلَى ٱلۡأَذۡقَانِ فَهُم مُّقۡمَحُونَ ۝٨ وَجَعَلۡنَا مِنۢ بَيۡنِ أَيۡدِيهِمۡ سَدّٗا وَمِنۡ خَلۡفِهِمۡ سَدّٗا فَأَغۡشَيۡنَٰهُمۡ فَهُمۡ لَا يُبۡصِرُونَ ۝٩ وَسَوَآءٌ عَلَيۡهِمۡ ءَأَنذَرۡتَهُمۡ أَمۡ لَمۡ تُنذِرۡهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ۝١٠ إِنَّمَا تُنذِرُ مَنِ ٱتَّبَعَ ٱلذِّكۡرَ وَخَشِيَ ٱلرَّحۡمَٰنَ بِٱلۡغَيۡبِۖ فَبَشِّرۡهُ بِمَغۡفِرَةٖ وَأَجۡرٖ كَرِيمٍ ۝١١ إِنَّا نَحۡنُ نُحۡيِ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَنَكۡتُبُ مَا قَدَّمُواْ وَءَاثَٰرَهُمۡۚ وَكُلَّ شَيۡءٍ أَحۡصَيۡنَٰهُ فِيٓ إِمَامٖ مُّبِينٖ ۝١٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. YA SIIN.

2. Na rantse da Alƙur'ani mai hikima.

3. Lalle kai (Manzon Allah) tabbas kana daga cikin manzanni.

4. (Kana) a kan tafarki madaidaici.

5. (Alƙur'ani) saukarwar (Allah) Mabuwayi Mai jin ƙai ne.

6. Don ka gargaɗi mutanen da ba a yi wa iyayensu gargaɗi ba, don haka kuwa suna cikin gafala.

7. Haƙiƙa hukuncin Allah (na azaba) ya wajaba a kan mafiya yawansu, don ba za su yi imani ba.

8. Lalle Mun sanya ƙuƙumai a wuyoyinsu har zuwa haɓoɓinsu, don haka kawunansu a ɗage suke.

9. Muka kuma sanya wani shamaki a gabansu da kuma shamaki a bayansu, sai Muka lulluɓe musu (idanuwa), don haka ba sa gani.

10. Kuma duk ɗaya ne a wurinsu ko ka yi musu gargaɗi ko ba ka yi musu gargaɗi ba, ba za su yi imani ba.

11. Kana yin gargaɗi ne kawai ga wanda ya bi umarnin Alƙur'ani, ya kuma ji tsoron Allah ba tare da ya gan Shi ba; sai ka yi masa albishir da samun gafara da lada na karamci.

12. Lalle Mu ne za Mu raya matattu, Muke kuma rubuta irin abubuwan da suka gabatar (a rayuwarsu) da kuma abin da suka bari a bayansu (bayan mutuwa). Kowane abu kuma Mun ƙididdige shi a cikin Lauhul-Mahafuzu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da haruffa guda biyu, watau 'Ya' da 'Sin', waɗanda suke ishara zuwa ga mu'ujizar Alƙur'ani. [Duba tafsirinmu na farkon *Suratul Bakara*].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da Alƙur'ani wanda ayoyinsa suke cike da hikima da zubi mai matuƙar tsari da azanci, wanda ƙarya ba ta zuwa masa ta gabansa ko ta bayansa. Sai kuma Allah ya tabbatar da manzancin Annabi (ﷺ) da cewa lalle shi yana ɗaya daga cikin manzannin da Allah ya aiko zuwa ga bayinsa don su umarce su da bautar sa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da wani ba, don haka ba shi ne farau cikin manzanni ba.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa Manzonsa (ﷺ) yana kan tafarki madaidaici, yana bin miƙaƙkiyar hanyar shari'a, kuma ita wannan hanyar saukakkiya ce daga Allah Mabuwayin Sarki wanda babu mai iya karawa da shi, mai rahama ga bayinsa muminai.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa manufar saukar masa da waccan shari'ar da ba shi Alƙur'ani mai girma ita ce, don ya yi wa Larabawa gargaɗi da shi, waɗanda wani annabi bai zo wa iyayensu ba, ya gargaɗe su a kan abin da suke aikatawa na shirka, don haka suna cikin gafala da ɗimuwa ta rashin sanin Tauhidi da imani. Kuma haka abin ya kasance game da duk wata al'umma wadda ta rasa mai yi mata gargaɗi, don haka takan zama cikin tsananin buƙatar aika mata da manzo domin nuna mata tafarki madaidaici.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa yawancin waɗanda ya aika wa manzanninsa suke kiran su zuwa bauta masa shi kaɗai da ƙaurace wa shirka, sun kafirce wa kiran annabawansu, sai azabar Allah ta tabbata a kansu, domin ba za su yi imani da Allah da Manzonsa ba, ba kuma za su yi aiki da gaskiyar da ta zo musu ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwatanta su da mutanen da aka sanya ƙuƙumi a wuyoyinsu aka haɗa hannayensu a ƙarƙashin haɓoɓinsu aka ɗaure tamau, sai ya zamanto dole ne su ɗaga kawunansu sama don ba za su iya yin ƙasa-ƙasa da su ba. To waɗannan mutane da aka ci galaba ne a kansu ba za su iya yin imani ba, kuma ba za su miƙa wuya ga Allah ba, kuma ba za su iya rusuna kawunansu gare shi ba.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara da bayyana cewa, ya sanya shamaki tsakaninsu a gabansu da kuma bayansu wanda ya katange su daga ba da gaskiya da amsa kiran Allah, ya kuma rufe idanunsu ba sa ganin gaskiya su amfana da ita. Wannan kuwa ya faru ne gare su bayan taurin kansu da dogewarsu a kan kafirci da bushewar zukatansu.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa, waɗannan kafiran ko ya yi musu gargaɗi ko kar ya yi musu gargaɗi duka ɗaya ne a gare su ba za su yi imani da gaskiyar da ya zo musu da ita daga Allah ba. Waɗanda kawai za su amfana da gargaɗinsa su ne waɗanda suka gaskata Alƙur'ani, suka kuma ji tsoron Allah ba tare da suna ganin sa ba, ko lokacin da suka kaɗaita babu mai ganin su sai Allah. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya yi wa duk wani mai irin wannan siffa albishir da samun gafara daga Allah da kuma wani babban lada wanda yake jiran sa a lahira, watau shiga Aljanna.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa zai tashi matattu don yi musu sakayya a kan ayyukansu, kuma shi ne yake rubuta duk abin da suka aikata a rayuwarsu ta duniya mai kyau ko mummuna, har ma da ayyukan da suka bar gurabensu masu kyau a bayan mutuwarsu, kamar sadaka mai gudana, ko marasa kyau kamar aikin kafirci, kuma ya ƙididdige komai a cikin littafin Lauhul Mahfuzu, ba abin da yake ɓuya gare shi.

An karɓo daga Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An samu ƙarin filayen da babu kowa a kusa da Masallacin Annabi (ﷺ) sai ƙabilar Banu Salima suka yi nufin dawowa kusa da Masallacin. Da labari ya kai ga Manzon Allah (ﷺ) sai ya ce musu: "Labari ya zo mini cewa kuna son ku dawo kusa da Masallaci?" Sai suka ce: "E, haka ne, mun so mu yi haka ya Manzon Allah." Sai ya ce: "Ya ku Banu Salima, ku yi zamanku a unguwanninku za a rubuta muku ladan tattakinku (watau na zuwa Masallaci)." [Muslim #665].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin ba da labarin waɗanda suka gabata yayin kira zuwa ga Allah.

2. Babu wani sahihin zance game da tantance sunan alƙaryar da aka ambata a wannan ƙissar. Wasu sun ce ita ce alƙaryar Anɗakiya da ke yankin Sham. Amma wasu daga cikin malamai sun raunana wannan magana saboda dalilai kamar haka:

Na ɗaya, abin da yake sananne a wurin Nasara shi ne mutanen Anɗakiya sun yi imani da Hawariyawa sun kuma bi su, don haka su ba a hallaka su ba. Waɗannan kuwa Allah ya bayyana cewa ya hallaka su.

Na biyu, sanannen abu a wurin Nasara shi ne Hawariyawa sun je wa mutanen Anɗakiya ne bayan ɗauke Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sannan kuma su biyu ne suka je ba uku ba, kuma ba sa ambaton Habibu An-Najjar ko zuwan wani mutum daga wuri mai nisa daga birni. Don haka waɗannan da aka ambata a nan ba Hawariyawa ne ba. Shaikhul Islam Ibn Taimiyya ya ce: "Wannan ita ce magana mafi inganci a wurin malaman Musulmi da manyan malaman tafsiri". [*Aljawabus-Sahih,* Juzu'i na 2 shafi na 245-246].

Na uku, waɗannan manzanni uku, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi ne ya aika su, bai ce Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne ya aika su ba.

Na huɗu, sanannen abu ne a wurin malamai cewa bayan saukar Attaura Allah bai hallaka wata al'umma da gamammiyar azaba ba irin yadda ya yi wa mutanen Annabi Nuhu ko Annabi Hudu ko Annabi Salihu. Wannan alƙaryar kuwa Allah ya hallaka su ne da wata azaba da ya saukar musu daga sama.

Na biyar, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a cikin Alƙur'ani bai ambaci wani manzo da wani ya aika ba, ya ambaci manzannin da shi ya aika ne.

Na shida, maganar da mutanensu suka faɗa musu cewa: "Ku mutane ne kamarmu", magana ce da kafirai suke faɗa wa manzannin da suka ce Allah ne ya aiko su ba waɗanda wani manzo ya aika ba. Wannan ya sanya a ƙarshen ƙissar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: "Abin takaici ga bayi shi ne, ba wani manzo da zai zo musu sai sun zamanto suna yi masa izgili."

Na bakwai, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan buga misali ne ga mushirikai da suka ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da yi musu gargaɗi da al'ummun da ya hallaka saboda sun ƙaryata wani manzo da ya aika musu kamar Manzon Allah (ﷺ). Amma ba ya ba da misali da waɗanda sahabban Manzon Allah (ﷺ) sun fi su daraja ba, domin a ittifaƙin malamai Abubakar da Umar da Usman da Aliyyu sun fi Hawariyawa daraja.

Na takwas, Allah ya bayyana cewa tsakanin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Muhammadu (ﷺ) babu wani manzo da aka aiko. [Dubi *Suratul Ma'ida*, aya ta 19].

3. Camfi aiki ne na kafirai.

4. Shiriya a hannun Allah take shi kaɗai, aikin manzanni kawai shi ne isar da saƙo.

Suratu Yasin (13-19)

وَٱضۡرِبۡ لَهُم مَّثَلًا أَصۡحَٰبَ ٱلۡقَرۡيَةِ إِذۡ جَآءَهَا ٱلۡمُرۡسَلُونَ ١٣ إِذۡ أَرۡسَلۡنَآ إِلَيۡهِمُ ٱثۡنَيۡنِ فَكَذَّبُوهُمَا فَعَزَّزۡنَا بِثَالِثٖ فَقَالُوٓاْ إِنَّآ إِلَيۡكُم مُّرۡسَلُونَ ١٤ قَالُواْ مَآ أَنتُمۡ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُنَا وَمَآ أَنزَلَ ٱلرَّحۡمَٰنُ مِن شَيۡءٍ إِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا تَكۡذِبُونَ ١٥ قَالُواْ رَبُّنَا يَعۡلَمُ إِنَّآ إِلَيۡكُمۡ لَمُرۡسَلُونَ ١٦ وَمَا عَلَيۡنَآ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ١٧ قَالُوٓاْ إِنَّا تَطَيَّرۡنَا بِكُمۡۖ لَئِن لَّمۡ تَنتَهُواْ لَنَرۡجُمَنَّكُمۡ وَلَيَمَسَّنَّكُم مِّنَّا عَذَابٌ أَلِيمٞ ١٨ قَالُواْ طَٰٓئِرُكُم مَّعَكُمۡۚ أَئِن ذُكِّرۡتُمۡۚ بَلۡ أَنتُمۡ قَوۡمٞ مُّسۡرِفُونَ ١٩

13. Kuma ka ba su misali da mutanen wata alƙarya lokacin da manzannin suka zo mata.

14. A yayin da Muka aika musu (manzanni) biyu sai suka ƙaryata su, sannan Muka ƙarfafe su da na uku, sai suka ce: “Lalle mu manzanni ne zuwa gare ku.”

15. Suka ce: “Ku ai ba kowa ba ne face mutane kamarmu, kuma (Allah) Mai rahama bai saukar da komai ba, ku dai ba abin da kuke yi sai ƙarya.”

16. Suka ce: “Ubangijinmu Yana sane da cewa mu lalle tabbas manzanni ne zuwa gare ku.

17. “Kuma babu wani abu a kanmu sai isar da aike bayyananne.”

18. Suka ce: “Mu dai lalle mun camfa ku, tabbas idan ba ku bari ba to za mu jefe ku, kuma tabbas za ku gamu da azaba mai raɗaɗi daga gare mu.”

19. Suka ce: “Camfinku ya ƙare a kanku. Yanzu don an yi muku gargaɗi ne (za ku faɗi haka?) A’a, ku dai mutane ne maɓarnata.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya ba wa kafirai masu ƙaryata shi labarin mutanen wata alƙarya da su ma suka ƙaryata manzannin da Allah ya aika musu suka yi jayayya da su, daga ƙarshe aka hallaka su baki ɗaya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya fara aika musu da manzanni biyu ne domin su kirawo su zuwa ga kaɗaita Allah da bauta, to amma sai suka ƙaryata su suka ƙi yin imani da su. Sai Allah ya ƙarfafe su da wani manzo na uku ko wannan zai taimaka su yi imani. Waɗannan manzanni uku suka shaida wa mutanen alƙaryar cewa, lalle su manzannin Allah ne da ya aiko su don su kirawo su zuwa kaɗaita Allah da bauta da bin dokokinsa.

To amma duk da haka sai mutanen alƙaryar suka ce, su fa ba za su yi imani da su ba, domin su ba su yarda an aiko su ba, saboda suna ganin su ma mutane ne kamarsu, ba su fi su da komai ba. Hasali ma dai ba su yarda cewa Allah ya saukar da wani wahayi daga sama ba, don haka su sun ɗauke su a matsayin masu yi wa Allah ƙarya suna cewa wai ya aiko su zuwa gare su.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mana martanin da manzannin nan uku suka mayar wa mutanen wannan alƙaryar yayin da suka tabbatar musu da cewa lalle Allah wanda ya aiko su ya san su manzanninsa ne, domin da ƙarya suke yi masa to da ya tona asirinsu ya kuma kunyata su. Don haka wannan ma kaɗai ya isa hujja a kan gaskiyar manzancinsu.

Sannan suka nuna musu cewa su ba wani abu suka zo nema a wurinsu ba, su kawai buƙatarsu ita ce su isar da saƙon Allah mabayyani a gare su, amma ba su ne masu kimsa shiriya a zukatan mutane ba, wannan aikin Allah ne shi kaɗai.

To amma maimakon mutanen alƙaryar su yi murna da wannan alheri da ya zo musu su miƙa wuya, sai kawai suka shiga tuhumar waɗannan manzanni uku da cewa sun jawo musu masifa da sharri, domin kuwa sun camfa su. Suka fara razana su da cewa, lalle idan ba su daina wannan wa’azin nasu na cewa a bauta wa Allah shi kaɗai ba a kuma yarda da manzancinsu, tabbas za su jefe su da duwatsu har lahira, kuma za su ɗanɗana musu azaba mai raɗaɗi.

Sai manzannin nan suka ba su amsa da cewa camfinsu a kansu zai ƙare, saboda kafircinsu da rashin imani da manzannin Allah da suka yi. Suka kuma nuna mamakinsu game da wannan furuci na kafirai, domin babu dalilin da zai sa su riƙa camfa mutanen da suke tunatar da su Allah suna gargaɗin su game da azabarsa. To amma ba komai ya jawo musu hakan ba sai zarmewa da suka yi wajen kafirci da saɓon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Son alheri ga mutane siffa ce daga cikin siffofin masu imani.

2. Wajabcin isar da da'awar Tauhidi da jure wa kowace irin wahala a kan haka.

3. Abubuwan da masu kira zuwa ga Tauhidi suke gamuwa da su na wahalhalu da barazana ga rayuwarsu.

4. Busharar da ake yi wa wanda ya yi shahada bayan mutuwarsa yayin da ake nuna masa gidansa na Aljanna da ni'imomin cikinta.

5. Ya kamata ga mai kira zuwa ga Allah ya guji neman abin hannun mutane, domin kare martabarsa da samar wa da'awarsa gurbi a zukatansu.

6. Wanda ya ƙagi halitta daga babu shi ne ya fi cancanta a bauta masa.

7. Tabbatar da tashi bayan mutuwa don komawa ga Allah ya yi wa kowa hisabi a kan ayyukansa.

8. Duk abin da bai mallaki amfanarwa ko cutarwa ba, to bai dace a bauta masa ba.

9. Wannan mutumin shi ne wanda ya yi wa mutanensa nasiha a lokacin rayuwarsa, ya kuma yi musu nasiha bayan mutuwarsa.

10. Imani shi ne yake sanya bawa ya sami gafarar Allah da karamcinsa.

11. Rundunar Allah tana da yawan gaske, mala'iku suna cikin rundunar Allah.

12. Bayanin girman Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Yasin (20-29)

وَجَآءَ مِنْ أَقْصَا ٱلْمَدِينَةِ رَجُلٌ يَسْعَىٰ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱتَّبِعُوا۟ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿٢٠﴾ ٱتَّبِعُوا۟ مَن لَّا يَسْـَٔلُكُمْ أَجْرًا وَهُم مُّهْتَدُونَ ﴿٢١﴾ وَمَا لِىَ لَآ أَعْبُدُ ٱلَّذِى
فَطَرَنِى وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٢٢﴾ ءَأَتَّخِذُ مِن دُونِهِۦٓ ءَالِهَةً إِن يُرِدْنِ ٱلرَّحْمَٰنُ بِضُرٍّ لَّا تُغْنِ عَنِّى شَفَٰعَتُهُمْ شَيْـًٔا وَلَا يُنقِذُونِ ﴿٢٣﴾ إِنِّىٓ إِذًا لَّفِى ضَلَٰلٍ
مُّبِينٍ ﴿٢٤﴾ إِنِّىٓ ءَامَنتُ بِرَبِّكُمْ فَٱسْمَعُونِ ﴿٢٥﴾ قِيلَ ٱدْخُلِ ٱلْجَنَّةَ ۖ قَالَ يَٰلَيْتَ قَوْمِى يَعْلَمُونَ ﴿٢٦﴾ بِمَا غَفَرَ لِى رَبِّى وَجَعَلَنِى مِنَ ٱلْمُكْرَمِينَ ﴿٢٧﴾ ۞ وَمَآ
أَنزَلْنَا عَلَىٰ قَوْمِهِۦ مِنۢ بَعْدِهِۦ مِن جُندٍ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَمَا كُنَّا مُنزِلِينَ ﴿٢٨﴾ إِن كَانَتْ إِلَّا صَيْحَةً وَٰحِدَةً فَإِذَا هُمْ خَٰمِدُونَ ﴿٢٩﴾

20. Wani mutum kuma ya zo daga can ƙarshen gari yana sauri ya ce: "Ya ku mutanena, ku bi waɗannan manzannin.

21. "Ku bi waɗanda ba sa tambayar ku wani lada, ga su kuma shiryayyu.

22. "Ni kuma me zai hana ni in bauta wa wanda Ya halicce ni, kuma gare Shi ne za a komar da ku?

23. "Yanzu na riƙi wasu ababen bauta ba Shi ba, alhali kuwa idan (Allah) Mai rahama Ya nufe ni da wata cuta, cetonsu ba zai amfana min komai ba, kuma ba za su iya tsamo ni ba?

24. "Lalle ni idan na yi haka to tabbas na zama cikin ɓata mabayyani.

25. "Lalle ni na yi imani da Ubangijinku, sai ku saurare ni."

26. Aka ce (da shi): "Shiga Aljanna." Ya ce: "Kaicon mutanena, ina ma da suna sane?

27. “Da gafarar da Ubangijina Ya yi min, Ya kuma sanya ni cikin waɗanda aka karrama?”

28. Ba Mu kuma saukar da wata runduna (ta mala’iku) a kan mutanensa daga sama ba a bayansa, ba Mu kuma saba saukarwa ba.

29. Ba abin da ya kasance sai tsawa guda ɗaya, sai ga su matattu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wani mutum daga wani wuri mai nisa na wannan birni wanda ya sami labarin da’awar waɗannan manzanni uku da yadda mutanensu suka ƙaryata su, ya zo don yi musu nasiha yana umartar su da su bi abin da waɗannan manzanni suka zo musu da shi. Ya tabbatar musu da cewa ba wani lada suke nema a wajensu ba, sun zo ne kawai don su isar musu da saƙon Allah, kuma su mutane ne shiryayyu masu bin tafarkin gaskiya, don haka ya dace su bi abin da suke kiran su a kai.

To amma duk da wannan nasiha da ya yi wa mutanensa, wannan bai sa sun yi imani ba, sai ma suka riƙa zargin sa da sukan sa game da bin waɗannan manzannin. Sai shi kuma ya mayar musu da martani cewa, me zai hana shi ya bauta wa Allah wanda ya ƙaga halittarsa, ya wadata shi da buƙatunsa, su ma kuma me zai hana su bauta wa Allah wanda ya halicce su kuma wurinsa ne gaba ɗaya za a mayar da su don ya yi musu hisabi a kan ayyukansu? Ya nuna musu rashin yardarsa da bautar wani ba Allah ba da cewa, yanzu ta yaya zai riƙi wasu abubuwan bauta ba Allah ba yana bauta musu? Waɗannan ababen bauta kuma ba su da wani amfani ko kaɗan, domin idan Allah mai rahama ya nufe shi da wani mummunan abu ba za su iya kare shi ba, domin cetonsu ba zai wadatar da shi da komai ba, ba kuma za su iya kuɓutar da shi daga azabar Allah ba idan har ya mutu a kan kafirci bai tuba ba. Don haka idan ya tsaya a kan bautar su ba Allah ba to lalle ya yi babban ganganci, domin ya bar wanda ya cancanci bauta ya kama wanda bai cancanta ba. Ya ma fito fili ya faɗa musu shi fa ya yi imani da Ubangijinsa kuma su ma shi ne Ubangijinsu, don haka su saurari nasiharsa su yi aiki da ita, kuma barazanar kisa da suke yi masa shi ba ta dame shi ba.

To amma sai suka kashe shi domin ganin ya matsa musu da nasiha, nan take bayan ya yi shahada sai aka ce masa ya shiga Aljanna. To yayin da ya shiga cikinta ya ga irin karamcin da aka yi masa da ɗimbin ni’imomi da aka tanadar masa sai ya yi burin ina ma a ce mutanensa waɗanda suka ƙaryata shi suka kuma kashe shi sun ga irin garaɓasar da yake ciki da gafarar zunubansa da ya samu da karamcin Ubangijinsa a gare shi, don su ma su yi imani su sami irin sakamakon da ya samu.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya hallakar da waɗannan kafirai da suka ƙaryata manzanninsa uku, suka kuma kashe mutumin da ya yi musu nasiha da cewa, bai buƙaci saukar da mala’iku daga sama ba don halaka su, domin a wurinsa al’amarin mai matuƙar sauƙi ne, sai kawai Allah ya ƙaddara hallakarsu ta zamanto tsawa guda ɗaya ce daga sama, kawai sai ga su a mace ba rai, kamar wutar da take ci balbal sai kawai a ga ta mutu murus ba ita ba alamarta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin takaici da nadamar da kafirai za su sami kansu a cikinta a ranar alƙiyama.

2. Haramcin yin izgili da Allah ko manzonsa ko addininsa. Mai yin haka in bai tuba ba zai gamu da nadama a ranar alƙiyama.

3. Ɗaukan darussa da izina daga rayuwar al’ummun da suka gabata, domin gani ga wane ya ishi wane tsoron Allah.

4. Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama da hisabi da sakamako.

Suratu Yasin (30-32)

يَٰحَسۡرَةً عَلَى ٱلۡعِبَادِۚ مَا يَأۡتِيهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ٣٠ أَلَمۡ يَرَوۡاْ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم مِّنَ ٱلۡقُرُونِ أَنَّهُمۡ إِلَيۡهِمۡ لَا يَرۡجِعُونَ٣١ وَإِن كُلٌّ لَّمَّا جَمِيعٞ لَّدَيۡنَا مُحۡضَرُونَ٣٢

30. Nadama ta tabbata ga bayi (masu ƙaryatawa), ba wani manzo da zai zo musu sai sun zamanto suna yi masa izgili.

31. Shin ba sa gani ne, al’ummu nawa ne Muka hallaka kafin su, cewa lalle kuwa ba sa dawowa zuwa gare su?

32. Kuma duk gaba ɗayansu wurinmu za a tattara su.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana matsayin kafiran da suke ƙaryata manzanninsa suke yi musu izgili da cewa, matsayi ne mai ban takaici da ban haushi, domin kuwa nadamarsu za ta yi tsawo a ranar alƙiyama inda ba za ta yi musu wani amfani ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara jan hankalinsu da cewa shin ba su ga abin izina ba game da al’ummun da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallakar gabaninsu, kuma sun riga sun mutu ba za su ƙara dawowa duniya ba, sun je sun tarar da ayyukansu da suka gabatar waɗanda Allah zai yi musu sakamako a kansu?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa duk al’ummu gaba ɗayansu za a tattaro su a gabansa, domin ya yi musu hukunci na adalci ba tare da an zalunci kowa da komai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin cikar Kudurar Allah da ikonsa na raya halittunsa bayan mutuwarsu, kamar yadda yake raya ƙasa bayan ƙeƙashewarta.

2. Kafa wa mutane hujja da abin da suke gani yau da gobe domin kawar musu da duk wata shakka.

3. Ni’imar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa da yake fitar musu da dangogin abincinsu da na dabbobinsu daga ƙasa, ba da wata dabara ko ƙarfinsu ba.

4. Wajabcin godewa a kan ni’imomin Allah na sarari da na ɓoye.

5. A cikin halittar dangogin abubuwa bibbiyu namiji da mace kuma, lallai akwai babbar aya da take nuna cikar Kudurar Allah da kamalarsa, da tsarkakarsa daga duk wani aibi ko nakasa.

Suratu Yasin (33-36)

وَءَايَةٞ لَّهُمُ ٱلۡأَرۡضُ ٱلۡمَيۡتَةُ أَحۡيَيۡنَٰهَا وَأَخۡرَجۡنَا مِنۡهَا حَبّٗا فَمِنۡهُ يَأۡكُلُونَ٣٣ وَجَعَلۡنَا فِيهَا جَنَّٰتٖ مِّن نَّخِيلٖ وَأَعۡنَٰبٖ وَفَجَّرۡنَا فِيهَا مِنَ ٱلۡعُيُونِ٣٤ لِيَأۡكُلُواْ مِن ثَمَرِهِۦ وَمَا عَمِلَتۡهُ أَيۡدِيهِمۡۖ أَفَلَا يَشۡكُرُونَ٣٥ سُبۡحَٰنَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡأَزۡوَٰجَ كُلَّهَا مِمَّا تُنۢبِتُ ٱلۡأَرۡضُ وَمِنۡ أَنفُسِهِمۡ وَمِمَّا لَا يَعۡلَمُونَ٣٦

33. Kuma wata aya ce a gare su (ganin) matacciyar ƙasar da Muka raya ta Muka fitar da ƙwaya daga gare ta, wadda kuma ita ce suke ci.

34. Muka kuma sanya gonaki na dabinai da na inabai a cikinta (ƙasar), Muka kuma ɓuɓɓugo da idanuwan ruwa daga gare ta.

35. Don su ci daga ‘ya’yan (itacenta) da kuma abin da hannanyensu suka aikata. Me ya sa ba za su riƙa godiya ba?

36. Tsarki ya tabbata ga wanda Ya halicci dangogin komai na maza da mata daga abin da ƙasa take tsirowa, kuma daga su kansu, da ma daga abin da ba su sani ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu manyan dalilai masu nuna cikar Kudurarsa ta iya tayar da matattu ya yi musu hisabi a ranar alƙiyama. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya nuna musu wata ayarsa game da ƙasar da ta riga ta ƙeƙashe, amma sai ya saukar mata ruwan sama ya raya ta da shi, ya fitar wa bayinsa dangogin tsirrai da shuke-shuke iri-iri wanda za su ci da wanda dabbobinsu za su ci. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sanya gonakin dabino da na inabi a cikin wannan ƙasar da ya raya da ruwan sama, sannan kuma ya ɓuɓɓugo da idanuwan ruwa daga cikinta wanda za a shayar da shuke-shuke da shi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu haka ne don su ci ‘ya’yan itatuwan da ya ni’imta su da su, ba don ƙarfinsu ko ƙwarewarsu ba, to me ya hana su gode wa Allah a kan wannan gagarumar ni’ima da ya yi musu, su bauta masa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da abokan tarayya ba, su kuma yi imani da manzanninsa?

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata hikima tasa da cewa, shi ne wanda ya halicci kowane jinsin abu bibiyu namiji da mace na tsirrai da shuke-shuke da ma su kansu mutane, ya kuma yi su maza da mata jinsi daban-daban, har ma da sauran wasu halittu da ba su sani ba, na kan tudu da na cikin ruwa. Babu shakka duk wanda yake da ikon yin irin wannan aiki, tabbas mai iko ne a kan tayar da matacce bayan mutuwarsa, kuma shi ne kaɗai ya cancanta a bauta masa ba tare da shirka ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tunatar da bayi ni’imar Allah ta samuwar dare da rana, domin gudanar da rayuwarsu yadda ya dace da buƙatunsu.

2. Rana gudu take a sararin samaniya a cikin falakinta ba a tsaye take a wuri guda ba.

3. Duk halittun da ke cikin sammai suna gudana ne bisa tsarin da Allah ya ɗora su a kansa, kuma babu mai kauce masa.

4. Bayanin girman Kudurar Allah da ke tattare da wata, ta yadda haskensa yake farawa da kaɗan-kaɗan, sannan ya yi ta ƙaruwa har girmansa ya cika, sannan ya dawo yana raguwa har ya koma ƙarami. Wannan yana nuna cikar Kudurar Allah. Da a ce ya ga dama da sai ya yi shi cikakke ko da yaushe, ko kuma ragagge a kowane lokaci.

Suratu Yasin (37-40)

وَءَايَةٌ لَّهُمُ ٱلَّيۡلُ نَسۡلَخُ مِنۡهُ ٱلنَّهَارَ فَإِذَا هُم مُّظۡلِمُونَ ٣٧ وَٱلشَّمۡسُ تَجۡرِي لِمُسۡتَقَرّٖ لَّهَاۚ ذَٰلِكَ تَقۡدِيرُ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡعَلِيمِ ٣٨ وَٱلۡقَمَرَ قَدَّرۡنَٰهُ مَنَازِلَ حَتَّىٰ عَادَ كَٱلۡعُرۡجُونِ ٱلۡقَدِيمِ ٣٩ لَا ٱلشَّمۡسُ يَنۢبَغِي لَهَآ أَن تُدۡرِكَ ٱلۡقَمَرَ وَلَا ٱلَّيۡلُ سَابِقُ ٱلنَّهَارِۚ وَكُلّٞ فِي فَلَكٖ يَسۡبَحُونَ ٤٠

37. Dare ma aya ne a gare su, wanda Muka sabule yini daga gare shi, sai ga su cikin duhu.

38. Rana kuma tana gudu zuwa wurin da aka iyakance mata. Wannan tsari ne na (Allah) Mabuwayi, Masani.

39. Wata kuma Mun ƙaddara masa masaukai, har ya koma kamar tsohuwar zarbar dabino.

40. Ba zai yiwu rana ta riski wata ba, dare kuma ba zai riga yini ba. Kowanne kuwa yana iyo ne a cikin falaki.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana manyan ayoyinsa masu nuna cikar Kudurarsa da girman ikonsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa kafirai cewa, dare ma wata aya ce a gare su da ke tabbatar da yiwuwar tashi bayan mutuwa, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gusar da rana daga dare sai kawai mutane su gan su a cikin duhu. Hakanan ma yakan kawar da wannan duhun na dare wanda ya game ko'ina da ina, sai kawai a ga rana ta fito ta haskaka sasannin ƙasa, kowa kuma sai ya fita neman abincinsa. Don haka ita rana haka take tutur tana gudu ne zuwa matabbatarta inda aka iyakance mata ba ta ƙetare shi, ba ta yin gaban kanta. Wannan gudu da take yi kuwa tsari ne na Allah mabuwayi cikin mulkinsa masanin ɗaukacin halittunsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya ƙaddara wa wata nasa masaukai, a kowane dare yana da nasa masauki har sanda girmansa ya cika, sannan ya dawo yana ƙanƙancewa har ya zama siriri sosai kamar zarbar dabino wadda saboda daɗewa ta sirance ta tanƙware ta zama kamar baka. Wannan ita ce alamar ƙarshen kwanakin kowane wata.

Sannan Allah ya tabbatar da cewa waɗannan ayoyi na rana da wata da dare da yini duka suna gudana ne a kan tsarin da ya ajiye su a kai, babu mai wuce iyakarsa, watau ba zai yiwu rana ta riski wata ba har ta canza masa hanyar tafiyarsa ko ta tafiyar da haskensa; hakanan ba zai yiwu dare ya riga yini har ya shiga cikinsa kafin ƙarewar lokacinsa ba. Duk waɗannan halittu da sauran manyan taurari kowanne cikinsu yana da hanyarsa ta musamman wadda aka tsara masa yake tafiya a kanta koyaushe da izinin Allah.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Na kasance a masallaci tare da Manzon Allah (ﷺ) lokacin faɗuwar rana sai ya ce: "Ya kai Abu Zarrin, ka kuwa san inda rana take faɗuwa?" Sai na ce: "Allah da Manzonsa ne mafi sani." Sai ya ce: "Lalle tana tafiya ne har sai ta yi sujjada a ƙarƙashin Al-Arshi, wannan shi ne faɗin Allah: "Rana kuma tana gudu zuwa matabbatarta, wannan tsari ne na Mabuwayi, Masani." [Bukhari #4802 da Muslim #159].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa 'yan'adam, yayin da ya tserar da iyayensu daga nutsewa a cikin ruwan Ɗufana zamanin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Da Allah ya ga dama da sai ya hallaka su baki ɗaya ya zamanto babu mutum ɗaya da zai yi saura a bayan ƙasa.

2. Daga cikin hanyoyin tarbiyyar Allah ga bayinsa akwai nuna musu ayoyi waɗanda za su yi musu jagora zuwa ga sanin abin da zai amfane su a rayuwarsu da addininsu.

3. Rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa yayin da ya samar musu ababen hawa daban-daban, sannan yake ba su kariya yayin da suke kan waɗannan ababen hawan har lokacin da za su sauka.

Suratu Yasin (41-44)

وَءَايَةٌ لَّهُمْ أَنَّا حَمَلْنَا ذُرِّيَّتَهُمْ فِى ٱلْفُلْكِ ٱلْمَشْحُونِ ﴿٤١﴾ وَخَلَقْنَا لَهُم مِّن مِّثْلِهِۦ مَا يَرْكَبُونَ ﴿٤٢﴾ وَإِن نَّشَأْ نُغْرِقْهُمْ فَلَا صَرِيخَ لَهُمْ وَلَا هُمْ يُنقَذُونَ ﴿٤٣﴾ إِلَّا رَحْمَةً مِّنَّا وَمَتَٰعًا إِلَىٰ حِينٍ ﴿٤٤﴾

41. Kuma wata aya ce a gare su cewa Mu Muka ɗauki iyayensu a cikin jirgin ruwa wanda aka maƙare.

42. Muka kuma halitta musu abin da suke hawa kwatankwacinsa.

43. Idan kuwa da Mun ga dama, sai Mu nutsar da su, don haka babu wani mai taimakon su, ba kuma za a kuɓutar da su ba.

44. Sai dai rahama daga gare Mu da kuma jin daɗi zuwa wani lokaci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya daɗa bayyana wata ayar ce mai nuna girman Kudurarsa da kuma rahamarsa ga bayinsa da cewa, shi ne ya tserar da zurriyar Annabi Adamu a zamanin Annabi Nuhu bayan ɓarkewar ruwan Ɗufana, a cikin jirgin ruwa wanda yake maƙare da halittun Allah daban-daban, kamar mutane da dabbobi da tsuntsaye waɗanda Allah ya umarci Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ɗauka a cikin jirgin; daga kowane jinsi kuma ya ɗauki namiji da mace.

Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wata ayarsa mai tabbatar da Kaɗaitakarsa da ni'imarsa ga bayinsa da cewa, shi ne ya halitta musu wasu ababen hawan daban bayan jirgin ruwa waɗanda suke hawa domin zirga-zirgarsu a tudu ko a ruwa.

Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda yake yalwata musu falalarsa a koyaushe, domin da ya ga dama da sai ya nutsar da su a cikin ruwan babu kuma mai iya taimaka musu ya hana shi abin da ya yi niyyar aikatawa ko ya tserar da su yayin da ya nutsar da su, sai dai idan shi ne ya nufe su da rahama sai ya kuɓutar da su su dawo su ci gaba da more rayuwar duniya zuwa ƙarshen taƙaitaccen lokacin da aka ƙayyade musu. Ya kuwa yi musu haka ne domin su ɗauki darasi da izina.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kiyaye dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne hanyar samun katari da rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Waɗanda suka riga suka yi nisa a cikin kafirci da saɓon Allah ba sa wa'azantuwa da duk wata aya da za a nuna musu ko wata hujja da za a kafa musu.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hore wa bayinsa ƙarfi da damar aikata kyawawan ayyuka da guje wa munanan ayyuka idan sun ga damar yin haka, don haka idan sun kauce hanya to wannan zaɓinsu ne ba Allah ne ya tilasa su ba.

4. Kafa hujja da ƙaddara domin barin aikata alheri ko kuma aikata sharri ɗabi'a ce ta kafirai.

Suratu Yasin (45-47)

وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱتَّقُواْ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيكُمۡ وَمَا خَلۡفَكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ٤٥ وَمَا تَأۡتِيهِم مِّنۡ ءَايَةٖ مِّنۡ ءَايَٰتِ رَبِّهِمۡ إِلَّا كَانُواْ عَنۡهَا مُعۡرِضِينَ ٤٦
وَإِذَا قِيلَ لَهُمۡ أَنفِقُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ قَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنُطۡعِمُ مَن لَّوۡ يَشَآءُ ٱللَّهُ أَطۡعَمَهُۥٓ إِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٤٧

45. Idan kuwa aka ce da su: "Ku kiyayi abin da yake gabanku da abin da yake bayanku, don a ji ƙan ku", (sai su bijire).

46. Babu wata aya daga ayoyin Ubangijinsu da za ta zo musu sai sun kasance masu bijire mata.

47. Idan kuma aka ce da su: “Ku ciyar daga abin da Allah Ya arzuta ku,” sai waɗanda suka kafirta su ce wa waɗanda suka yi imani: “Yanzu ma ciyar da wanda, da Allah Ya ga dama da ya ciyar da shi? Ba abin da kuke ciki in ban da ɓata mabayyani.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai suka yi ta bijire wa Allah duk da ayoyin da yake nuna musu da tsoratarwar da yake yi musu da cewa, duk sanda aka gargaɗe su game da ranar lahira wadda suke fuskanta da abubuwan ban tsoro da ke cikinta, aka kuma yi musu kashedi game da duniya wadda suke ba ta baya, domin fatan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu baiwa da rahamarsa, sai su ƙi sauraron abin da ake gaya musu, su yi watsi da duk wani gargaɗi da ake yi musu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk ƙokacin da ayoyin Allah suka zo musu masu ɗauke da dalilai a kan Tauhidi da bayanin bautar Allah shi kaɗai, sai su bijire musu su ƙi tsayawa su wa’azantu da su.

Sannan kuma idan an neme su da su taimaki talakawa da mabuƙata da dukiyar da Allah ya arzuta su da ita sai su yi ƙememe, har ma su riƙa faɗin wai don me za a ce su taimaka wa wasu, ai tunda aka gan su a cikin talauci da rashi, to da ma haka Allah yake son ya gan su, domin da ya ga dama ai shi ne zai ciyar da su ba su ba, don haka wai su ba za su yarda su saɓa wa muradin Allah ba. Suka kuma nuna wa muminai cewa umarnin da suke yi musu na ciyar da wasu kuskure ne ƙarara, kuma ba gaskiya ne ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da tashi ranar lahira.

2. Tabbatar da busa ƙaho ta farko da ta biyu.

3. Zuwan alƙiyama ba zato ba tsammani.

4. Cikar adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga kowa da kowa.

Suratu Yasin (48-54)

وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٤٨ مَا يَنظُرُونَ إِلَّا صَيۡحَةٗ وَٰحِدَةٗ تَأۡخُذُهُمۡ وَهُمۡ يَخِصِّمُونَ ٤٩ فَلَا يَسۡتَطِيعُونَ تَوۡصِيَةٗ وَلَآ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِمۡ يَرۡجِعُونَ ٥٠ وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَإِذَا هُم مِّنَ ٱلۡأَجۡدَاثِ إِلَىٰ رَبِّهِمۡ يَنسِلُونَ ٥١ قَالُواْ يَٰوَيۡلَنَا مَنۢ بَعَثَنَا مِن مَّرۡقَدِنَاۜ هَٰذَا مَا وَعَدَ ٱلرَّحۡمَٰنُ وَصَدَقَ ٱلۡمُرۡسَلُونَ ٥٢ إِن كَانَتۡ إِلَّا صَيۡحَةٗ وَٰحِدَةٗ فَإِذَا هُمۡ جَمِيعٞ لَّدَيۡنَا مُحۡضَرُونَ ٥٣ فَٱلۡيَوۡمَ لَا تُظۡلَمُ نَفۡسٞ شَيۡـٔٗا وَلَا تُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٥٤

48. Suna kuma cewa: “Yaushe ne wannan alƙawarin, idan kun kasance masu gaskiya?”

49. Ba abin da suke sauraro sai tsawa guda ɗaya da za ta far musu, a yayin da suke cikin hayaniyar rayuwa.

50. Don haka ba za su sami damar yin wata wasiyya ba, kuma za su iya koma wa wajen iyalinsu ba.

51. Aka kuma busa ƙaho, sai ga su suna fitowa daga ƙaburbura zuwa wurin Ubangijinsu.

52. Suka ce: “Kaiconmu, wane ne ya tashe mu daga makwancinmu?” (Sai a ce da su): “Ai wannnan shi ne abin da (Allah) Mai rahama Ya yi alƙawarinsa, manzanni kuma sun yi gaskiya.”

53. Ba abin da zai kasance sai tsawa guda ɗaya, sai ga su gaba ɗaya an tattaro su gabanmu.

54. To a yau fa ba za a zalunci wani rai da komai ba, ba kuma za a saka muku ba sai da irin abin da kuka zamanto kuna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin yadda kafirai suke ƙaryata zuwan ranar alƙiyama, suna ganin ba gaskiya muminai suke faɗa musu ba yayin da suke gargaɗin su game da zuwan wannan rana, da abubuwan tsoro da ta ƙunsa, har ma suna yi musu izgili da cewa yaushe ne ma ranar za ta zo, domin an daɗe ana yi musu alƙawarin zuwanta amma su har yanzu shiru suke ji.

Sai aka mayar musu da martani cewa, ba abin da suke sauraro sai busar ƙaho ta farko da mala'ika zai yi, sai kwatsam ba zato ba tsammani suna tsaka da hayaniyarsu ta rayuwa, kamar ciniki ko noma ko kiwo da sauransu, sai ta auko musu ba shiri.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yayin da wannan busar ƙahon ta shammace su, to ba za su sami damar ko da yin wasiyya ga junansu ba, ba ma za su iya komawa gidajensu wajen iyalansu ba, a nan take za su mutu.

Daga nan kuma sai a yi busa ta biyu domin tashi, to a nan ne mutane za su riƙa fitowa daga ƙaburburansu cikin gaggawa a firgice domin yi musu hisabi da sakamako.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a wannan ranar kafirai masu ƙaryata tashin alƙiyama za su shiga cikin takaici da nadama, har ma suna tambayar cewa, wane ne ya tashe su daga ƙaburburansu? To sai a amsa musu da cewa, ai da ma wannan shi ne abin da Allah ya yi alƙawarin aukuwarsa, ga shi kuwa ya auku, kuma manzannin Allah sun yi gaskiya a kan duk abin da suka isar na saƙon Ubangijinsu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar da cewa al'amarin tashin halittu da ransu daga ƙaburbura ba wani abu ne mai wahalarwa ko ɗaukan wani lokaci a wajensa ba; kawai busa ce ta biyu za a yi a ƙaho sai duk halittu gaba ɗaya su tattara gaban Allah domin yi musu hisabi.

A wannan ranar kuma hukunci za a yi na adalci ga kowa da kowa, ba wani da za a zalunce shi ko a tauye wa masu haƙƙi haƙƙinsu, ba kuma za a ƙara wa wani laifin da bai aikata ba; kowa za a saka masa da abin da ya aikata a duniya na alheri ko na sharri.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman ni'imar 'yan Aljanna wadda za ta shagaltar da su ba za su riƙa tuna komai da ya danganci 'yan wuta ba.

2. Daga cikin ni'imomin 'yan Aljanna akwai matayen da Allah zai tanadar musu waɗanda za su rayu tare da su cikin inuwoyin Aljanna.

3. A Aljanna babu rana sai inuwa.

4. Duk abin da 'yan Aljanna za su nema za su same shi.

5. Daga cikin mafi girman ni'imar da 'yan Aljanna za su dace da ita ita ce gaisuwa da sallamar Ubangiji a gare su. Wannan yana nuna za su ji muryarsa (Mai tsarki da ɗaukaka) ne kai tsaye.

Suratu Yasin (55-58)

إِنَّ أَصۡحَٰبَ ٱلۡجَنَّةِ ٱلۡيَوۡمَ فِي شُغُلٖ فَٰكِهُونَ ٥٥ هُمۡ وَأَزۡوَٰجُهُمۡ فِي ظِلَٰلٍ عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِ مُتَّكِـُٔونَ ٥٦ لَهُمۡ فِيهَا فَٰكِهَةٞ وَلَهُم مَّا يَدَّعُونَ ٥٧ سَلَٰمٞ قَوۡلٗا مِّن رَّبّٖ رَّحِيمٖ ٥٨

55. Lalle ‘yan Aljanna a yau suna cikin shagali, suna masu farin ciki.

56. Su da matansu suna cikin inuwoyi kishingiɗe a kan gadaje.

57. Suna da kayan marmari a cikinta, suna kuma da duk irin abin da suke nema.

58. Sallama (za a riƙa yi musu), **magana ce daga Ubangiji Mai rahama**.

A waɗannan ayoyi kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon muminai ne a lahira, inda ya nuna cewa ‘yan Aljanna a ranar za su zamanto cikin shagali na ni’ima, babu tunanin wasu abubuwa a gabansu, saboda ni’imomin da aka tanadar musu na Aljanna da babban rabo da za su samu, don haka a ranar cike suke da murna da jin daɗi, suna kishingiɗe tare da matansu a kan karagu na alfarma cikin inuwoyin Aljanna. Wannan yana nuna kamalar hutu da nutsuwa da jin daɗi marar iyaka da za su samu a wannan ranar.

Bugu da ƙari kuma za a tanadar musu kayan marmari iri-iri, kamar inabi da rumman da ɓaure. Duk wani abu da za su buƙata na jin daɗi da morewa, za su same shi ba tare da wata wahala ko ɓata lokaci ba.

Sannan abin da ya fi komai daɗi da za su dace da shi a wannan rana shi ne, sallama daga Allah Ubangijinsu. Da zarar sun samu kai wa ga wannan, to sun sami duk wani aminci da jin daɗin da babu kamarsa, domin sun dace da gaisuwar da babu abin da ya kai ta daraja da ɗaukaka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Za a wulaƙanta kafirai a ranar alƙiyama a hana su shiga cikin mutanen ƙwarai.

2. Duk wanda bai bauta wa Allah shi kaɗai ba, to Shaiɗan ya bauta wa. Don haka duk masu bautar wanin Allah cikin kowace irin kama ne to sun yi tarayya da juna wajen bautar Shaiɗan domin umarninsa suka bi.

3. Tsananin gabar Shaiɗan ga ɗan’adam.

4. Duk wanda ya bi Shaiɗan har ya ɓatar da shi, to ba shi da hankali.

5. Tabbatar da samuwar wutar Jahannama, kuma za a nuna wa kafirai ita a ranar alƙiyama tun kafin su shige ta.

6. Cikar adalcin Ubangiji yayin da zai ba wa gaɓoɓin ɗan’adam damar su ba da shaida a kansa kafin a hukunta shi da laifinsa.

7. Cikar Kudurar Allah ta ba wa gaɓoɓi dama su yi magana ya toshe bakunansu.

8. Nuni ga mutum a kan ya yi gaggawa ya mori rayuwarsa ta hanyar yin aiki nagari lokacin ƙarfinsa kafin rauni na tsufa ya zo masa.

Suratu Yasin (59-68)

وَٱمۡتَٰزُواْ ٱلۡيَوۡمَ أَيُّهَا ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٥٩ *أَلَمۡ أَعۡهَدۡ إِلَيۡكُمۡ يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ أَن لَّا تَعۡبُدُواْ ٱلشَّيۡطَٰنَۖ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ٦٠ وَأَنِ ٱعۡبُدُونِيۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٦١ وَلَقَدۡ أَضَلَّ مِنكُمۡ جِبِلّٗا كَثِيرًاۖ أَفَلَمۡ تَكُونُواْ تَعۡقِلُونَ ٦٢ هَٰذِهِۦ جَهَنَّمُ ٱلَّتِي كُنتُمۡ تُوعَدُونَ ٦٣ ٱصۡلَوۡهَا ٱلۡيَوۡمَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡفُرُونَ ٦٤ ٱلۡيَوۡمَ نَخۡتِمُ عَلَىٰٓ أَفۡوَٰهِهِمۡ وَتُكَلِّمُنَآ أَيۡدِيهِمۡ وَتَشۡهَدُ أَرۡجُلُهُم بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٦٥ وَلَوۡ نَشَآءُ لَطَمَسۡنَا عَلَىٰٓ أَعۡيُنِهِمۡ فَٱسۡتَبَقُواْ ٱلصِّرَٰطَ فَأَنَّىٰ يُبۡصِرُونَ ٦٦ وَلَوۡ نَشَآءُ لَمَسَخۡنَٰهُمۡ عَلَىٰ مَكَانَتِهِمۡ فَمَا ٱسۡتَطَٰعُواْ مُضِيّٗا وَلَا يَرۡجِعُونَ ٦٧ وَمَن نُّعَمِّرۡهُ نُنَكِّسۡهُ فِي ٱلۡخَلۡقِۚ أَفَلَا يَعۡقِلُونَ ٦٨

59. Kuma (za a ce): “Ku ware a yau, ya ku waɗannan masu manyan laifuka.”

60. Yanzu ban umarce ku ba, ya ku ‘yan’adam, da cewa kada ku bauta wa Shaiɗan; lalle shi maƙiyi ne mai bayyana (ƙiyayya)?

61. Kuma ku bauta min. Wannan shi ne tafarki madaidaici.

62. Haƙika kuma (Shaiɗan) ya ɓatar da halittu masu yawa; shin ba za ku hankalta ba?

63. Wannan ita ce Jahannamar da ta kasance ana yi muku alƙawarinta.

64. Ku shige ta a yau saboda kafircin da kuke yi.

65. A yau za Mu toshe bakunansu, hannayensu su yi mana magana, ƙafafuwansu kuma su ba da shaidar irin abin da suka kasance suna aikatawa.

66. Da kuma Mun ga dama da sai Mu shafe idanuwansu su riƙa rige-rigen hawan siraɗi, to ta yaya za su iya gani (a wannan lokaci)?

67. Da kuma Mun ga dama da sai Mu jirkita halittarsu a inda suke, saboda haka ba za su iya ci gaba da tafiya ba, ba kuma za su iya dawowa ba.

68. Wanda kuma Muka tsawaita rayuwarsa, za Mu mayar da halittarsa baya; me ya sa ne ba sa hankalta?.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon kafirai waɗanda suka ƙaryata manzanninsa da ranar alƙiyama da cewa, a ranar ne za a umarce su da su ware daga cikin muminai domin bai dace da su su cakuɗu da bayin Allah na gari ba, domin sakamakonsu daban-daban ne, kamar yadda ayyukansu suke daban-daban.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zarge su da bijire masa da bin Shaiɗan. Ya tunatar da su wasiyyar da ya yi musu ta hanyar manzanninsa da cewa kada su kuskura su bi Shaiɗan su riƙa aikata kafirci da ayyukan saɓo, domin shi Shaiɗan babban maƙiyinsu ne mai bayyana ƙiyayyarsa gare su a fili. To ina hankalinsu ya tafi da har suka rungume shi suna yi masa biyayya?

Sannan ya tabbatar musu cewa, ya umarce su da su bauta masa shi kaɗai kada su haɗa kowa da bautarsa, domin bautarsa da yi masa biyayya ita ce hanya miƙaƙƙiya wadda za ta kai su ga shiga Aljanna da samun yardar Allah. To amma sai suka yi watsi da wannan wasiyya ta Ubangiji suka saɓa masa, suka kuma bi Shaiɗan maƙiyinsu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗakar da su cewa Shaiɗan fa ya ɓatar da mutane masu yawa, wanda hakan abin mamaki ne, domin ina hankulansu suke da ba za su gane cewa kamata ya yi su bauta wa Allah shi kaɗai ba su guji biyayya ga Shaiɗan babban maƙiyinsu?

To tunda sun kafirce wa Allah sun ƙi kaɗaita shi da bauta sun zaɓi su bi Shaiɗan to a ranar alƙiyama za a nuna musu wutar Jahannama wadda aka yi ta yi musu gargaɗi a kanta a duniya suna ƙaryatawa. Hujjarsu wai don ba su gan ta ba; to a yau ga ta ga su suna ganin ta ƙuru-ƙuru. Sai a umarce su da su shiga cikinta su ƙuna da tsananin zafinta saboda kafircin da suka yi a duniya.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a ranar ne zai toshe bakunansu ba za su iya musanta abin da suka aikata na kafirci da saɓon Allah ba. Hannayensu da sauran gaɓɓansu ne za su riƙa magana suna ba da shaidar duk abin da suka aikata a duniya.

An karɓo daga Anas ɗan Malik ya ce: “Mun kasance a wurin Manzon Allah (ﷺ) sai ya yi dariya, sai ya ce: “Shin ko kun san me nake yi wa dariya?” Sai muka ce: “Allah da Manzonsa ne mafi sani.” Sai ya ce: “Ina dariya ne a kan yadda bawa zai magana da Ubangijinsa, zai ce: “Ya Ubangijina, ashe ba ka kare ni daga zalunci ba?” Sai Allah ya ce: “E, haka ne, na kare ka.” Sai bawa ya ce: “To ni ban yarda wani ya ba da shaida a kaina ba sai wani ɓangare na jikina.” Sai Allah ya ce: “Kai kanka a yau ka isa mai shaida a kanka, hakanan mala’iku masu girma marubuta su ma sun isa shaidu.” Annabi (ﷺ) ya ce: “Sai a toshe bakinsa sai a ce wa gaɓoɓinsa: “Ku yi magana.” Sai su yi magana su ba da labarin ayyukansa, sai kuma a ba shi damar yin magana, sai ya ce: “Tir da ku, dominku ne nake wannan fafutukar.” [Muslim #2969].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa da ya ga dama da sai ya shafe idanuwansu kamar yadda ya toshe bakunansu, sai su daina ganin komai, sannan ya umarce su da su yi rige-rigen hawan siraɗi domin su ƙetara zuwa Aljanna, amma ina! Ba za su iya ba bayan an shafe idanunsu.

Sannan Allah ya bayyana cewa, da ya ga dama da ya jirkita halittarsu ya mayar da su sandararru ta yadda ba za su iya barin inda suke ba, ba kuma za su iya gaba ko baya ba domin su guje wa faɗawa wutar Jahannama.

Abin nufi a nan shi ne, su dai waɗannan kafirai azabar Allah ta riga ta tabbata a kansu, dole ne su gamu da mummunan sakamakonsu. A wurin da suke kuwa babu komai sai wutar da aka fito musu da ita a fili ƙarara suka gan ta. Babu kuma mai iya kuɓuta daga faɗawa cikinta sai dai ta hanyar tsallake siraɗi, hakan kuwa ba zai samu ba sai ga muminai waɗanda za su riƙa tafiya a cikin haskensu. Amma su kafirai babu wata dama da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ba su ta samun kuɓuta daga wuta. To idan Allah ya ga dama sai ma ya shafe idanunsu, ya kuma dankwafar da su su kasa motsawa nan da can, ba za su iya gane inda siraɗin yake ba ballantana su tsallaka shi su wuce zuwa Aljanna, ba kuma za su iya yin gaba ko baya ba ballantana su tsere wa azabar wuta, don haka babu makawa sai sun shige ta.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da ɗan’adam cewa tsawon rai ba shi ne zai hana shi mutuwa ba, wanda ma Allah ya ba shi tsawon rai, to zai mayar da halittarsa baya ne, ya koma ya yi rauni na jiki da na ƙwaƙwalwa, don haka me ya hana waɗannan kafiran su yi tunani su gane cewa duniya ba matabbata ce ba; gida na har abada shi ne gidan lahira?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi (ﷺ) ba mawaƙi ne ba, kuma bai dace da haka ba, domin matsayin annabta ba ƙarami ne ba, ballantana matsayinsa na shugaban halittu duka.

2. Annabi ba ya ƙirƙirar waƙe da kansa, amma yakan iya rera waƙen da wasu suka ƙirƙira; yin haka kuma ba ya mayar da mutum mawaƙi.

3. Babbar manufar saukar da Alƙur'ani ita ce, don a gargaɗi masu rayayyar zuciya da shi a yi musu wa'azi da ayoyinsa.

4. Babu mai amfana da Alƙur'ani sai mai rayayyar zuciya.

Suratu Yasin (69-70)

وَمَا عَلَّمۡنَٰهُ ٱلشِّعۡرَ وَمَا يَنۢبَغِي لَهُۥٓۚ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ وَقُرۡءَانٞ مُّبِينٞ ٦٩ لِّيُنذِرَ مَن كَانَ حَيّٗا وَيَحِقَّ ٱلۡقَوۡلُ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧٠

69. Ba Mu kuma koyar da shi (Muhammadu) waƙa ba, kuma ba za ta yiwu ba gare shi. (Abin da ya zo da shi) ba wani abu ba ne sai wa'azi da kuma Alƙur'ani mabayyani.

70. Don ya gargaɗi wanda ya kasance rayayye (wato mumini), azaba kuma ta tabbata a kan kafirai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar wa da mushirikai martani a kan tuhumar da suka yi wa Alƙur'ani ne cewa waƙa ce, wai shi kuma Manzon Allah mawaƙi ne. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi bai koya wa Manzonsa waƙa ba, kuma waƙa ma ba ta dace da shi ba, domin yawancin mawaƙa taɓaɓɓu ne kuma sai taɓaɓɓu ne suke bin su; shi kuwa shiryayye ne mai cikakken hankali, don haka yanayinsa ma bai yi kama da na mawaƙa ba ballantana har a ce masa mawaƙi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa abin da yake koyarwa ba wani abu ba ne face wa'azi da kuma Alƙur'ani mabayyani ga duk wanda yake da hankali na lura da haka.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa an saukar wa Manzo (ﷺ) Alƙur'ani ne domin ya gargaɗi duk wani mai rayayyar zuciya mai hasken basira, domin shi kaɗai ne zai amfana da shi, su kuma kafirai azabar Allah ce za ta tabbata a kansu bayan an tsayar musu da hujja da saukar da Alƙur'ani, don haka ba su da sauran wani hanzari a wurin Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafa wa bayi hujja a kan Kaɗaitakar Allah da ni'imomin da suke gani, suna ta'ammali da su yau da gobe.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci dabbobin ni'ima ne domin amfanin ɗan'adam, kuma wani ɓangare ne na manyan ni'imominsa masu tarin yawa a gare shi.

3. Tabbatar wa da Allah siffar hannu bisa yadda ya dace da girmansa, ba tare da kwatance ko kamanceceniya ko tawili ba.

4. Ya halatta a yi amfani da dabbobin ni'ima kamar raƙuma wajen hawa, amma ba tare da cutar da su ba.

5. Wajabcin godiya ga Allah a kan dukkan ni'imominsa.

Suratu Yasin (71-73)

أَوَ لَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّا خَلَقۡنَا لَهُم مِّمَّا عَمِلَتۡ أَيۡدِينَآ أَنۡعَٰمٗا فَهُمۡ لَهَا مَٰلِكُونَ ٧١ وَذَلَّلۡنَٰهَا لَهُمۡ فَمِنۡهَا رَكُوبُهُمۡ وَمِنۡهَا يَأۡكُلُونَ ٧٢ وَلَهُمۡ فِيهَا مَنَٰفِعُ وَمَشَارِبُۖ أَفَلَا يَشۡكُرُونَ ٧٣

71. Yanzu ba sa gani ne cewa Mu Muka halitta musu dabbobin ni'ima daga abin da hannanyenmu suka aikata, sai ga su suna mallakar su?

72. Muka kuma hore musu su, don haka ababen hawansu daga cikinsu ne, kuma daga gare su suke ci.

73. Suna kuma da wata moriya da abin sha daga gare su. Yanzu ba za su riƙa godiya ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya janyo hankalin kafirai masu bautar waninsa da su duba su ga dabbobin ni'ima da ya halitta musu, waɗanda suka mallaki damar sarrafa su yadda suke buƙata ba tare da wata wahala ba. Ya kuma hore musu waɗannan dabbobi suna miƙa wuya gare su, suna sarrafa su yadda suka ga dama, su hau wasu su ɗora wa wasu kayansu masu nauyi, su yanka wasu daga cikinsu su ci namansu. Bayan wannan kuma sukan ci moriyarsu ta fuskoki daban-daban, kamar amfani da gashin raƙuma da na tumakai da fatunsu, domin shimfiɗa da kayan sawa. Hakanan sukan sayar da su su mori dukiyoyinsu. Sannan kuma sukan samu abin sha a tattare da su kamar nonon shanu ko na raƙuma ko na ƙananan dabbobi. To amma me ya hana su gode wa Allah wanda ya albarkace su da waɗannan ni'imomi masu ɗimbin yawa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Masu bautar wanin Allah suna yi ne a kan tsammanin za su amfane su a rayuwarsu, su kuma taimaka musu a duk lokacin da suke da buƙatar taimako. Hakanan duk wani maɓarnaci Shaiɗan yana kitsa masa a zuciyarsa tunanin amfanin abin da yake aikatawa, don ya doge a kan wannan aikin ya ƙi sauraron masu yi masa nasiha.

2. Kwantar wa da Manzon Allah hankali da tsoratar da mushirikai da sanar da su cewa, Allah yana sane da duk wani makirci da suke ƙullawa.

Suratu Yasin (74-76)

وَٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ ءَالِهَةً لَّعَلَّهُمۡ يُنصَرُونَ ٧٤ لَا يَسۡتَطِيعُونَ نَصۡرَهُمۡ وَهُمۡ لَهُمۡ جُندٞ مُّحۡضَرُونَ ٧٥ فَلَا يَحۡزُنكَ قَوۡلُهُمۡۘ إِنَّا نَعۡلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعۡلِنُونَ ٧٦

74. Suka kuma riƙi wasu ababen bauta ba Allah ba, don a taimaka musu.

75. Ba za su iya taimakon su ba, su da gumakan nasu duka ababen tattarawa ne (cikin wuta).

76. To kada maganarsu ta baƙanta maka. Lalle Mu Muna sane da abin da suke ɓoyewa da kuma abin da suke bayyanawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana butulcin kafirai ne waɗanda suka rungumi wasu abubuwan bauta ba Allah ba, suna kuma bauta musu tuƙuru sun yi watsi da kaɗaita Allah da bauta. A tsammaninsu waɗannan alloli za su taimaka musu su kuɓutar da su daga azabar Allah idan ya yi nufin azabtar da su. Sun jahilci cewa waɗannan allolin ba sa iya taimaka wa kawunansu ma ballantana su taimaka wa wani; a ƙarshe ma da su da allolin duk za a tattaro su ne zuwa wuta, a lokacin da suke nesanta kansu da juna.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) ya kwantar masa da hankali game da ƙaryata shi da kafirai suke yi suna cewa, shi ba Manzon Allah ne ba, ko kuma shi mawaƙi ne da sauran tuhumce-tuhumce da suke yi masa. Allah ya gaya masa cewa kada maganganunsu su baƙanta masa rai; yana sane da duk abin da suke ɓoyewa da wanda suke bayyanawa, kuma lalle zai yi musu sakayya a kansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin ɗabi'ar ɗan'adam yawan jayayya.

2. Samar da mutum daga ruwan maniyyi ya fi ban al'ajabi a kan samar da shi daga rududdugaggun ƙasusuwa. Wanda ya iya yin samarwa ta farko me zai hana shi ya iya yin ta biyu?

3. Tabbatar da tashi bayan mutuwa.

4. Halaccin amfani da hujjoji na hankali, don tabbatar da gaskiya da rushe ƙarya.

5. Tabbatar wa da Allah cikakken mulki da cikakkiyar Kudura ta sarrafa komai yadda ya ga dama.

Suratu Yasin (77-83)

أَوَ لَمۡ يَرَ ٱلۡإِنسَٰنُ أَنَّا خَلَقۡنَٰهُ مِن نُّطۡفَةٖ فَإِذَا هُوَ خَصِيمٞ مُّبِينٞ ٧٧ وَضَرَبَ لَنَا مَثَلٗا وَنَسِيَ خَلۡقَهُۥۖ قَالَ مَن يُحۡيِ ٱلۡعِظَٰمَ وَهِيَ رَمِيمٞ ٧٨ قُلۡ يُحۡيِيهَا ٱلَّذِيٓ أَنشَأَهَآ أَوَّلَ مَرَّةٖۖ وَهُوَ بِكُلِّ خَلۡقٍ عَلِيمٌ ٧٩ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُم مِّنَ ٱلشَّجَرِ ٱلۡأَخۡضَرِ نَارٗا فَإِذَآ أَنتُم مِّنۡهُ تُوقِدُونَ ٨٠ أَوَ لَيۡسَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يَخۡلُقَ مِثۡلَهُمۚ بَلَىٰ وَهُوَ ٱلۡخَلَّٰقُ ٱلۡعَلِيمُ ٨١ إِنَّمَآ أَمۡرُهُۥٓ إِذَآ أَرَادَ شَيۡـًٔا أَن يَقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٨٢ فَسُبۡحَٰنَ ٱلَّذِي بِيَدِهِۦ مَلَكُوتُ كُلِّ شَيۡءٖ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٨٣

77. Yanzu mutum ba ya gani cewa Mu Muka halicce shi daga maniyyi, sai ga shi ya zama mai jayayya a fili?

78. Ya kuma buga mana misali, kuma ya manta da halittarsa (yayin da) ya ce: "Wane ne zai raya ƙasusuwa, alhali kuma sun rududduge?

79. Ka ce: "Wannan da Ya fare su tun farko Shi ne zai raya su; Shi kuwa Masanin kowacce irin halitta ne.

80. "Wanda kuma Ya samar muku wuta daga koriyar bishiya, sai ga shi kuna hura wuta daga gare ta."

81. Yanzu wanda Ya halacci sammai da ƙasa ba zai zama Mai ikon halitta irinsu ba? Ai tabbas zai iya, kuma Shi ne Mai yawan yin halitta, Masani.

82. Umarninsa kawai idan Ya yi nufin wani abu sai Ya ce da shi: "Kasance", sai ya kasance.

83. To tsarki ya tabbata ga wanda mulkin kowane abu yake a hannunsa, kuma wurinsa ne kawai za a komar da ku.

A ayoyi na ƙarshen wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da martani ne ga masu jayayya a kan Kudurar Allah ta sake tayar da matattu cikin wata sabuwar halitta, kuma ya ja hankalin ɗan'adam cewa ya duba ya ga yadda asalin halittarsa take. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicce shi ne daga ɗigon ruwan maniyyi wulaƙantacce, wanda ya bi mataki daban-daban wasu bayan wasu har ya zama mutum daidaitacce, aka busa masa rai, har aka haife shi ya taso tun yana ƙarami har ya girma, sai kuma ga shi yanzu ya zama mai yawan jayayya da mahaliccinsa. Me zai hana shi ya dubi irin tazarar da take tsakanin yanayinsa na farko lokacin da yake maniyyi da kuma yadda ya koma daga ƙarshe? Ashe wannan bai isa ya zama dalili mai nuna cikar Kudurar Allah a kan sake dawo da shi bayan mutuwa ba?

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kafircin ɗan'adam ya kai shi ga manta wannan ƙwaƙƙwaran dalili har ta kai shi ga kafa hujja da rududdugaggun ƙasusuwa na matattu cewa, wai wane ne zai dawo da su su koma masu rai. Ya manta da ikon wanda ya ƙirƙire su daga babu.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya amsa musu da cewa, wanda ya halicci waɗannan rududduga ggun ƙasusuwa da farko, shi ne kuma wanda zai sake raya su, domin kuwa wanda ya halicce su a karon farko ba zai gagare shi ya dawo musu da ransu ba. Wannan

hujja ta farko kenan.

Hujja ta biyu, shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) masanin kowacce irin halitta ne, dangane da yanayi da kuma lokacin kowace halitta. Don haka mai cikakken ilimi na halitta irin haka yaya zai gagare shi ya dawo wa da matacce ransa duk sanda ya ga dama?

Hujja ta uku, shi ne wanda ya samar da wuta daga ɗanyar bishiya, watau ya haɗa abubuwa biyu kishiyoyin juna a wuri guda, ga lemar da ke jikin ɗanyar bishiya ya kuma nufi wuta ta kama a jikinta. Babu shakka wanda yake da ikon yin haka, tabbas yana da cikakken ikon da zai raya matattu.

Hujja ta huɗu, shi ne wanda ya halicci sammai da ƙasa da duk abin da ke cikinsu duk kuwa da girmansu da yalwarsu. Yanzu yaya za a ce ba zai zama mai ikon raya matattu ba bayan mutuwarsu? Lalle shi kaɗai ne mai wannan ikon. Hasali ma halittar ɗan'adam ta fi sauƙi gare shi a kan halittar sammai da ƙasa.

Hujja ta biyar, Allah shi ne mahaliccin dukkan halittu manya da ƙanana; babu wani mahaluƙi da halittarsa za ta gagare shi, kuma shi masanin komai ne babu abin da yake ɓuya a gare shi. To ta yaya zai kasa tayar da matattu?

Hujja ta shida, shi kaɗai ne ya kaɗaita da ikon cewa, idan ya yi nufin samar da kowane abu sai kawai ya ce masa 'ya samu', sai kuwa ya samu kamar yadda Allah yake nufinsa. Don haka raya matacce ma yana ƙarƙashin wannan iko nasa, saboda haka wannan ba zai gagare shi ba.

Hujja ta bakwai, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkaka daga duk wata nakasa ko aibi da mushirikai suke danganta shi da shi, kamar gajiyawa ko kasawa, domin kuwa shi ne mamallakin komai, shi yake sarrafa komai yadda yake so, makullan komai suna hannunsa, komai a ƙarƙashin ikonsa yake, saboda haka dawo wa da matattu rayukansu abu ne mai matuƙar sauƙi a wurinsa, kuma dukkansu zuwa gare shi za a mayar da su domin yi musu hisabi da sakamako.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da ikon ya rantse da duk abin da ya ga dama cikin halittunsa, don ya jawo hankula zuwa ga fahimtar girman sha'aninsu ko ɗaukar wata izina da darasi daga gare su. Amma wani mahaluƙi bai halatta ya yi rantsuwa ba sai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kawai.

2. Falalar mala'ikun Allah.

3. Mala'iku suna da ayyuka daban-daban da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗora musu, kowanne daga cikinsu kuma yana yin aikinsa ba tare da wata matsala ba.

4. Girman sha'anin Tauhidi.

5. Kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu, da rana da wata da sauran halittu na sama da na ƙasa, to hakanan shi kaɗai ya cancanta a bauta masa kada a haɗa shi da komai wajen bautarsa.

37-Suratus Saffat

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ta shahara da suna '*Suratus Saaffat*' , ba ta da wani suna na biyu da ya inganta ban da wannan. An kuma kira ta da wannan suna ne saboda zuwan lafazin'*Saaffat'* a cikinta, wanda kuma yake nufin mala'iku masu yin sahu-sahu.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin dukkan malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta hamsin da shida (56) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratul An'am'* gabanin '*Suratu Lukman*'.

4. Adadin ayoyinta:
Ayoyinta ɗari da tamanin da biyu ne (182) a wurin yawancin malamai. Amma a lissafin malaman Basra ayoyinta ɗari da tamanin da ɗaya ne (181).

5. Babban Jigonta:
Tsarkake Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) daga ƙarairayin da mushirikai suke danganta masa na samuwar alaƙa tsakaninsa da aljanu wadda suke cewa daga ita ne aka samu mala'iku.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tabbatar da Kaɗaitakar Allah da ƙarfafan hujjoji a kan haka.
• Tabbatar da tashi bayan mutuwa da sakamakon ayyukan bayi.
• Kwatanta kiran Annabi Muhammadu (ﷺ) ga mutanensa da kiran sauran annabawa ga al'ummunsu da bayanin yadda Allah ya taimaki manzanninsa da ɗaukaka darajarsu.
• Bayyana falala da darajar wasu daga cikin manzannin Allah.
• Dangogin uƙubar da Allah ya yi wa al'ummun da suka gabata bayan sun ƙaryata annabawansu.
• Rushe aƙidun mushirikai da ƙaryata da'awarsu ta cewa mala'iku 'ya'yan Allah ne mata.
• Alƙawarin nasara da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) kamar yadda ya taimaki manzannin da suka gabata.

Suratus Saffat (1-5)

وَٱلصَّٰٓفَّٰتِ صَفًّا ۝١ فَٱلزَّٰجِرَٰتِ زَجْرًا ۝٢ فَٱلتَّٰلِيَٰتِ ذِكْرًا ۝٣ إِنَّ إِلَٰهَكُمْ لَوَٰحِدٌ ۝٤ رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا وَرَبُّ ٱلْمَشَٰرِقِ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ina rantsuwa da mala’iku masu yin sahu-sahu.

2. Sannan da masu yi wa girgije tsawa.

3. Da masu karanta maganar Allah.

4. Lalle Ubangiijnku tabbas Ɗaya ne.

5. Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, kuma Ubangijin wuraren hudowar rana.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da yin rantsuwa da mala’ikunsa masu tsayawa sahu-sahu suna bautar sa.

An karɓo daga Jabiru ɗan Samura (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Yanzu ba za ku riƙa tsai da sahunku kamar yadda mala’iku suke tsai da sahu a wajen Ubangijinsu ba?” Sai muka ce: “Yaya mala’iku suke tsai da sahu a wajen Ubangijinsu?” Sai ya ce: “Suna cika sahu-sahu na farko, sannan suna daidaita a cikin sahu.” [Muslim #430 da Abu Dawud #661 da Nasa’i #816 da Ibn Majah #992].

An karɓo daga Huzaifa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “An fifita mu a kan sauran mutane da abu uku: An sanya tsayuwar sahunmu kamar tsayuwar sahun mala’iku; an sanya mana bayan ƙasa gaba ɗayanta ta zama masallaci; an kuma sanya mana turɓayarta ta zama abin tsarki idan mun rasa ruwa.” [Muslim #522].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da rantsuwa da mala’iku masu yi wa girgije tsawa su kora shi zuwa inda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ga damar ya saukar da ruwansa. Ya kuma rantse da mala’iku masu karanta maganar Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin waɗannan rantse-rantse da ya yi da cewa lalle abin bautar mutane ɗaya ne, shi ne Allah Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, kuma Ubangijin rana da wuraren hudowarta da faɗuwarta a tsawon shekara, ba shi da abokin tarayya wajen halittar waɗannan abubuwa da sarrafa su da gudanar da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci amfani iri biyu na taurari a sama:
Na ɗaya, zamantowarsu wani ado a sama, ba don su ba da sama ta zama duhu ne ƙirin, to sai Allah ya sanya taurari a cikinta domin duka sasanninta su yi haske ta riƙa ba da sha’awa ga duk mai kallon ta, matafiya a sahara, ko a kan ruwa kuma su yi amfani da su domin gane hanya cikin duhun dare.
Na biyu, tsaron sama daga duk wani shaiɗani mai taurin kai, wanda hatsabibancinsa zai kai shi ga satar sauraron maganganun mala’iku a sama, yayin da za a jefe su da garwashin wuta masu ƙuna domin hallaka su.

2. Shaiɗanun aljannu masu taurin kai ne da bijire wa Allah.

3. Shaiɗanu sukan iya satar jin kaɗan daga tattaunawar mala’iku a sama, amma ba za su sami cikakken sauraro ba.

4. Garwashin wuta mai fitowa daga taurari, akan jefi shaiɗanu da shi domin hana su satar sauraron maganganun mala’iku a sama.

5. Su ma aljannu akan yi musu azaba da wuta yayin da suka saɓa wa Allah mahaliccinsu.

Suratus Saffat (6-10)
إِنَّا زَيَّنَّا ٱلسَّمَآءَ ٱلدُّنْيَا بِزِينَةٍ ٱلْكَوَاكِبِ ۝٦ وَحِفْظًا مِّن كُلِّ شَيْطَٰنٍ مَّارِدٍ ۝٧ لَّا يَسَّمَّعُونَ إِلَى ٱلْمَلَإِ ٱلْأَعْلَىٰ وَيُقْذَفُونَ مِن كُلِّ جَانِبٍ ۝٨ دُحُورًا وَلَهُمْ عَذَابٌ وَاصِبٌ ۝٩ إِلَّا مَنْ خَطِفَ ٱلْخَطْفَةَ فَأَتْبَعَهُۥ شِهَابٌ ثَاقِبٌ ۝١٠

6. Lalle Mun ƙawata sama ta kusa da ado na taurari.

7. Da kuma tsaro daga dukkan wani shaiɗan mai tsaurin kai.

8. Ba kuma za su iya jiyowa ba (daga asirin) mala’iku na sama, sai a yi ta jifan su ta kowane ɓangare.

9. Don kora; suna kuma da wata azaba dawwamamma.

10. Sai dai wanda ya yi fautowar jin, to sai wani tauraro mai haske da ƙuna ya biyo shi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya ƙawata sama ta kusa da ƙasa da ado na taurari masu matuƙar haske da sheƙi kamar gwalagwalai.
Ya kuma bayyana wani muhimmanci na waɗannan taurarin bayan ado da suka yi wa sama, domin da su ne Allah yake tsare saman daga duk wani shaiɗani mai taurin kai da bijire wa ɗa’ar Allah, da su ne ake jifan irin wannan shaiɗanu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa su waɗannan shaiɗanu masu taurin kai ba za su iya jiyo maganar mala’iku ba a sama yayin da suke ambaton wani wahayi da Allah ya yi musu wanda ya danganci shari’arsa ko ƙaddararsa, za a yi ta jifan su ne da garwashin wuta ta kowane ɓangare don a kore su a hana su sauraron maganar mala’iku, sannan kuma a lahira suna da wata azaba mai raɗaɗi ta dindindin.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi togaciya ta wani daga cikin shaiɗanun wanda zai samu damar waftar wata kalma daga cikin tattaunawar mala’iku a kan wani abu da ba wani mahaluƙi a ƙasa da yake da masaniya a kansa, to shi ma bai tsira ba sai wani gargwashi mai haske da ƙuna ya bi shi domin ƙona shi.
Tana yiwuwa ya samu damar jefa wa ‘yan’uwansa shaiɗanu wannan kalmar kafin garwashin ya cim masa ya ƙona shi, su kuma su isar wa bokaye wannan batu, daga nan su kuma bokaye su gauraya shi da ƙarairayi ɗari su gaya wa mutanensu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da tashi bayan mutuwa.

2. Bayanin ƙarfin Kudurar Allah wanda babu abin da yake gagarar sa.

3. Idan kafirai sun yarda da cewa Allah ne ya halicci sammai da ƙasa da sauran manyan halittu, to don me suke ƙaryata cewa zai iya tashin su bayan mutuwarsu? Wannan ma ƙaramin aiki ne idan an kwatanta shi da waɗancan halittu.

4. Ishara zuwa ga asalin halittar ɗan’adam. Allah ya halicce shi ne daga wani taɓo mai daɗo.

5. Kafirai da suka ƙaryata gaskiya ba su tsaya iya nan ba, har sai da suka ƙara dulmiya cikin ɓatansu suka shiga yi wa muminai izgili da ba'a.

6. Idan zuciya ta riga ta ƙeƙashe to duk wani wa'azi ba ya amfanar ta, duk wani dalili kuma ba ya gamsar da ita.

7. Kafirai masu ƙaryata ranar alƙiyama za a tashe su ƙaskantattu wulaƙantattu. Wannan yana nuna su kuma muminai za a tashe su a mutunce tare da girmamawa.

8. Tabbatar da busa ƙaho ta biyu wadda duk halittu za su fito daga cikin ƙaburburansu don sauraron sakamako.

Suratus Saffat (11-19)
فَٱسْتَفْتِهِمْ أَهُمْ أَشَدُّ خَلْقًا أَم مَّنْ خَلَقْنَآ ۚ إِنَّا خَلَقْنَٰهُم مِّن طِينٍ لَّازِبٍۭ ﴿١١﴾ بَلْ عَجِبْتَ وَيَسْخَرُونَ ﴿١٢﴾ وَإِذَا ذُكِّرُوا۟ لَا يَذْكُرُونَ ﴿١٣﴾ وَإِذَا رَأَوْا۟ ءَايَةً يَسْتَسْخِرُونَ ﴿١٤﴾ وَقَالُوٓا۟ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا سِحْرٌ مُّبِينٌ ﴿١٥﴾ أَءِذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَٰمًا أَءِنَّا لَمَبْعُوثُونَ ﴿١٦﴾ أَوَ ءَابَآؤُنَا ٱلْأَوَّلُونَ ﴿١٧﴾ قُلْ نَعَمْ وَأَنتُمْ دَٰخِرُونَ ﴿١٨﴾ فَإِنَّمَا هِىَ زَجْرَةٌ وَٰحِدَةٌ فَإِذَا هُمْ يَنظُرُونَ ﴿١٩﴾

11. Ka tambaye su cewa, yanzu su suka fi ƙarfin halitta ko kuwa waɗanda a da Muka halitta? Lalle Mu Mun halicce su daga wani taɓo mai danƙo.

12. A'a, kai dai ka yi mamakin (ikon Allah da ƙaryatawarsu) ne, su kuma suna yin izgili.

13. Idan kuma aka yi musu wa'azi ba sa wa'azantuwa.

14. Idan kuma suka ga wata aya sai su tsananta ba'a.

15. Su kuma ce: "Wannan ba wani abu ba ne in ban da sihiri mabayyani.

16. "Yanzu idan muka mutu muka zama ƙasa da ƙasusuwa shin da gaske za a tashe mu?

17. "Haka ma da iyayenmu na farko?"

18. Ka ce: "Na'am, (za a tashe ku) kuna kuwa ƙaskantattu."

19. To (wannan) ba wani abu ba ne sai kawai tsawa guda ɗaya, sai ga su suna sauraron (abin da zai faru).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) ya tambayi mushirikai masu ƙaryata tashi bayan mutuwa, shin yanzu halittarsu ce ta fi ƙarfi ko kuma jikinsu da gaɓoɓinsu ne suka fi sauran abubuwan da Allah ya halitta ƙarfi, kamar sammai da ƙasa da mala'iku da taurari da sauran manya-manyan halittun Allah? Su kansu mushirikan sun tabbata ba za a taɓa gwada halittarsu da ta waɗancan ba, domin su Allah ya halicce su ne daga wani taɓo mai danƙo, to me ya sa za su riƙa ƙaryata tashi bayan mutuwa alhali ga shi daga irin abin da aka halicce su mai rauni da laushi?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Manzonsa (ﷺ) cewa ba ma sai ya tambaye su ba domin su mutane ne masu taurin kan tsiya, wannan tambayar ma ba amfanar su za ta yi ba, don ba sa yin duba zuwa ga dalilan da suke nuna cikar ikon Allah da kamalar Kudurarsa har su yi mamakin wannan dalilai.

Allah ya bayyana cewa Manzonsa ne zai yi mamakin Kudurarsa da yadda yake gudanar da al'amuran halittarsa, kuma shi ne yake mamakin yadda mushirikai suke ƙaryata tashi bayan mutuwa, saboda zaƙewarsu wajen ƙaryata hakan, har suke haɗawa da yin izgili. Idan ma an yi musu wa'azi a kan haka to ba sa amfana da duk gargaɗin da ake yi musu saboda zukatansu sun riga sun ƙeƙashe. Wannan ya sa duk wata ayar da za su gani daga cikin ayoyin da suke tabbatar da gaskiyar Manzon Allah sai su daɗa sa ƙaimi wajen izgili da ba'a, har ma suna nuna mamakinsu a kan haka, suna cewa Annabi Muhammadu (ﷺ) bai zo musu da komai ba in ban da sihiri bayyananne. Suna kuma mamakin wai a ce yanzu idan sun mutu sun zama ƙasa da rududdugaggun ƙasusuwa wai a ce za a sake tayar da su da ransu; suna ganin wannan ba abu ne da zai yiwu ba. Kuma ma abin da yake ƙara ba su mamaki shi ne wai a ce har iyayensu ma da suka mutu shekaru aru-aru su ma za a tashe su?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya tabbatar musu da cewa, tabbas za a tashe su ko da kuwa sun mutu sun zama ƙasa da ƙasusuwa rududdugaggu, kuma za a tashe su ne suna ƙaskantattu a ranar alƙiyama, domin kuwa tashinsu da rai ba abu ne mai wata wahala ba; kawai busa ɗaya ce Mala'ika Israfilu zai yi a cikin ƙaho, watau busa ta biyu, sai su tashi gaba ɗayansu suna kallon abubuwan ban tsoro na wannan ranar, suna kuma sauraron abin da Allah zai yi da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirai a lahira za su yi nadama amma marar amfani.

2. A ranar alƙiyama za a tattara duk wasu masu jinsin laifi ɗaya a wuri guda sannan a tarkata su zuwa Jahannama.

3. Taron gamayyar masu laifi iri ɗaya a lahira ba zai yi musu wani amfani ba, kamar yadda a nan duniya masu manufa iri ɗaya sukan haɗu domin kare kansu da taimakawa junansu.

Suratus Saffat (20-26)
وَقَالُواْ يَٰوَيۡلَنَا هَٰذَا يَوۡمُ ٱلدِّينِ ٢٠ هَٰذَا يَوۡمُ ٱلۡفَصۡلِ ٱلَّذِي كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ٢١ ٱحۡشُرُواْ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ وَأَزۡوَٰجَهُمۡ وَمَا كَانُواْ يَعۡبُدُونَ ٢٢ مِن
دُونِ ٱللَّهِ فَٱهۡدُوهُمۡ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلۡجَحِيمِ ٢٣ وَقِفُوهُمۡۖ إِنَّهُم مَّسۡـُٔولُونَ ٢٤ مَا لَكُمۡ لَا تَنَاصَرُونَ ٢٥ بَلۡ هُمُ ٱلۡيَوۡمَ مُسۡتَسۡلِمُونَ ٢٦

20. Sai su ce: "Kaitonmu!" (Sai a ce da su): "Wannan ita ce ranar sakamako.

21. "Wannan ita ce ranar hukunci wadda kuka kasance kuna ƙaryatawa."

22. (Za a ce da mala'iku): "Ku tattaro waɗanda suka yi zalunci su da abokan haɗinsu (shaiɗanu) da kuma abin da suka kasance suna bauta wa.

23. Waɗanda ba Allah ba, sai ku nuna musu hanyar zuwa wutar Jahima.

24. "Kuma ku tsayar da su; don lalle za a tambaye su.

25. "Cewa: 'Me ya sa ba kwa taimakon juna ne?'"

26. Ba haka ba ne, su dai a yau masu miƙa wuya ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ranar alƙiyama kafirai masu ƙaryata wannan rana za su shiga nadama marar amfani, da takaici su tabbatar da cewa wannan fa ita ce ranar sakamako wadda Allah yake saka wa bayinsa a kan duk wani aiki da suka gabatar a rayuwarsu ta duniya. Sai a ƙara tabbatar musu da cewa wannan ita ce ranar hukunci tsakanin bayi wadda suke ƙaryata zuwanta. Sannan kuma a wannan ranar ne za a umarci mala'iku da su tattara azzalumai waɗanda suka yi wa Allah shirka da duk wasu masu kama da su da masu ƙaryatawa a haɗa su tare da gumakan da suke bauta wa, sai a nuna musu hanyar shiga wuta. Amma kafin su kora su zuwa cikinta sai sun tsare su, domin a yi musu hisabi, game da kafircinsu da duk laifukan da suka aikata a duniya.
Daga nan sai a daka musu tsawa a ce da su me ya sa a nan ba sa taimakon junansu kamar yadda suka riƙa riyawa a duniya, suna cika bakin cewa gumakansu ne za su taimake su.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa a ranar babu maganar su taimaki juna; dukkansu za su miƙa wuya ne ga Allah su sallama, domin ba su da sauran wata dabara ko ƙarfi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A koyaushe masu ɓatar da mutane sukan fito musu ne ta hanyoyin alheri, sukan nuna wa mutane su masu son taimaka musu da tallafa wa rayuwarsu ne, kamar taimako na ilimi ko na jin ƙai ko lafiya. Ta irin waɗannan hanyoyi ne suke yaudarar mutane sai su ɓatar da su daga hanyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Duk wanda yake da raunin imani, ko kuma bai gina shi a kan wani ingantaccen tushe ba, to ba wuya akan ruɗe shi a hallaka shi ba tare da ya ankara ba.

3. Duk waɗanda suka bi shugabanninsu a kan ɓata, to a ranar alƙiyama sai sun rabu baram-baram, kowa na tuhumar ɗan'uwansa da laifi, yana la'antar sa.

4. Tsoratarwa game da zama da ɓatattu waɗanda suka kauce wa shari'ar Allah; waɗannan ba wuya sun ɓatar da duk wani wanda yake tare da su kamar yadda su ma suka ɓace.

5. Haɗarin girman kai, wanda shi ne ya jawo hallakar mushirikai yayin da suka bijire wa faɗar '*La ilaha ilal Lahu*' saboda girman kai da nuna isa.

6. Mushirikai sun ƙi yarda su furta Kalmar Shahada domin sun san ma'anarta, shi ne su kakkaɓe bautar komai sai bautar Allah shi kaɗai, don haka suka ƙi karɓar ta. Wannan ya nuna ba kawai faɗar ta da fatar baki ne ba zai sa ta amfani mutum, har sai ya yi aiki da ma'anarta ya ƙaurace wa bautar duk wani abu ba Allah ba, ya tsantsanta bautarsa ga Allah shi kaɗai.

Suratus Saffat (27-37)
وَأَقۡبَلَ بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖ يَتَسَآءَلُونَ ٢٧ قَالُوٓاْ إِنَّكُمۡ كُنتُمۡ تَأۡتُونَنَا عَنِ ٱلۡيَمِينِ ٢٨ قَالُواْ بَل لَّمۡ تَكُونُواْ مُؤۡمِنِينَ ٢٩ وَمَا كَانَ لَنَا عَلَيۡكُم مِّن سُلۡطَٰنِۖ بَلۡ كُنتُمۡ قَوۡمٗا طَٰغِينَ ٣٠ فَحَقَّ عَلَيۡنَا قَوۡلُ رَبِّنَآۖ إِنَّا لَذَآئِقُونَ ٣١ فَأَغۡوَيۡنَٰكُمۡ إِنَّا كُنَّا غَٰوِينَ ٣٢ فَإِنَّهُمۡ يَوۡمَئِذٖ فِي ٱلۡعَذَابِ مُشۡتَرِكُونَ ٣٣ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَفۡعَلُ بِٱلۡمُجۡرِمِينَ ٣٤ إِنَّهُمۡ كَانُوٓاْ إِذَا قِيلَ لَهُمۡ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ يَسۡتَكۡبِرُونَ ٣٥ وَيَقُولُونَ أَئِنَّا لَتَارِكُوٓاْ ءَالِهَتِنَا لِشَاعِرٖ مَّجۡنُونِۭ ٣٦ بَلۡ جَآءَ بِٱلۡحَقِّ وَصَدَّقَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٣٧

27. Shashinsu kuma ya fuskanci shashi suna tambayar juna.

28. Suka ce: "Lalle kun kasance kuna zo mana ta damanmu (don mu amince muku)."

29. Suka ce: “A’a, ba ku dai kasance muminai ba ne.

30. “Kuma mu ba mu da wani iko a kanku; ku dai kawai kun kasance mutane ne masu ɗagawa.

31. “Saboda haka faɗar Ubangijinmu (ta azaba) ta tabbata a kanmu; (cewa) lalle tabbas za mu ɗanɗana kuɗarmu.

32. “Don haka muka ɓatar da ku, domin mu ma lalle mun kasance ɓatattu ne.”

33. Saboda haka su a wannan ranar, masu tarayya ne a cikin azaba.

34. Lalle Mu kamar haka Muke yi wa masu manyan laifuka.

35. Lalle sun kasance idan aka ce da su: “Babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah,” sai su yi girman kai.

36. Su kuma riƙa cewa: “Yanzu ma bar allolinmu don wani mawaƙi mai taɓin hankali?”

37. Ba haka ba ne, ya dai zo ne da gaskiya, ya kuma gaskata manzanni.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da za a tattara mushirikai shugabanni da mabiya a cikin wutar Jahannama, za su fuskanci juna ne, rigima da zargi su kaure a tsakaninsu. Mabiya ne za su zargi shugabanninsu da cewa a duniya sun riƙa yaudarar su da daɗin baki, suna ɓullo musu ta fuskar addini da nuna cewa su masu gaskiya ne, suna ƙawata musu shirka da saɓon Allah, suka kuma hana su bin gaskiya da yarda da abin da manzanni suka zo musu da shi daga Allah. To su ma shugabannin sai su mayar musu da martini, su ƙaryata su, su nuna ba haka lamarin yake ba; su da ma suna kan ɓata da kafirci ne, ba su taɓa yin imani ba sai dai su ƙaryata manzanninsu. Kuma su ba wani ƙarfi suka nuna musu ba, suka sa su kafirta dole; kawai dai su mabiyan mutane ne masu zaƙewa cikin kafirci da ɓata da saɓon Allah, don haka, 'za mu ce ta tarar da mu je mu'.
Don haka sai suka tabbatar wa da mabiyansu cewa duk gaba ɗayansu maganar Allah ce ta azaba ta tabbata a kansu, saboda haka za su ɗanɗani azaba tare ba makawa, domin da su shuwagabannin da mabiyansu duka ɓatattu ne, kuma abin da ya cancanta da su ke nan.
Suka nuna musu cewa, waɗannan su ne dalilansu da suka sanya suka ɓatar da su, suka riƙa kiran su zuwa ga kafirci da ɓata, domin su ma da man ɓatattu ne ba sa kan tafarkin shiriya, don haka marar abu ba ya bayar da shi ga wani. Watau sai su daina zargin su su zargi kansu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa gaba ɗayansu shugabannin da mabiyan nasu za su yi tarayya a cikin azaba ranar alƙiyama, kamar yadda a duniya suka haɗu a kan kafirci da shirka da Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa, kamar yadda ya yi wa waɗannan irin wannan sakamakon azaba, haka zai yi wa duk wasu masu manyan laifuka na kafirci da haɗa shi da wasu wajen bauta.
Allah kuma ya bayyana mummunan laifin da suka aikata wanda ya jawo musu wannan sakamako, watau tun a duniya idan aka neme su da yin Kalmar Shahada su ce: ‘*La ilaha illal Lahu*’ kuma su yi aiki da ita su watsar da bautar duk wani abu ba Allah ba, sai su yi watsi da wannan kira saboda girman kai na ƙin gaskiya, suna ma cewa, ta yaya wai za su bar bautar allolinsu su kama maganar wani mawaƙi mai taɓin hankali? Suna nufin Manzon Allah (ﷺ). Sai Allah ya mayar musu da martani cewa shi Annabi Muhammadu (ﷺ) ba mawaƙi ne ba kuma ba mai taɓin hankali ba; Annabin Allah ne da ya zo musu da Alƙur’ani wanda yake kiran su zuwa ga kaɗaita Allah da bin Manzonsa, kuma ya gaskata sauran manzanni a kan saƙon da suka zo da shi daga Allah na Tauhidi da tabbatar da ranar alƙiyama kuma bai saɓa musu da komai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman martabar masu tsantsanta bauta ga Allah shi kaɗai, shi ya sa Allah ya danganta su da kansa ya kira su da ‘bayinsa’.

2. Muhimmancin ikhlasi, watau tsantsanta ibada ga Allah shi kaɗai, domin shi ne ke sanya wa Allah ya zaɓi bawa ya tsarkake shi.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai arzuta ‘yan Aljanna da dangogin arziki da suka sani a duniya, watau ta fuskar suna kawai, amma sun sha bamban ta fuskar ɗanɗano da kuma daɗi da ƙayatarwa.

4. Za a karrama ‘yan Aljanna ta fuskoki daban-daban: Mala’iku za su karrama su; samari masu yi musu hidima za su karrama su, sannan mafi girman karramawa da za su samu ita ce ta samun ganin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da samun yardarsa ta har abada.

5. Zaman ‘yan Aljanna zama ne na mutunta juna da kyakkyawar alaƙa, don haka ne ko wajen zamansu a kan gadajen Aljanna sukan fuskanci juna ne babu mai ba wa ɗan’uwansa baya.

6. Giyar Aljanna ba irin ta duniya ce ba; ita ba ta sanya ciwon kai kuma ba ta sanya maye.

7. Bayanin tsananin kyan matan Aljanna da tsananin ƙaunarsu ga mazajensu, ba sa kuma tunanin kowa sai su.

Suratus Saffat (38-49)

إِنَّكُمۡ لَذَآئِقُواْ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡأَلِيمِ ٣٨ وَمَا تُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٣٩ إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلۡمُخۡلَصِينَ ٤٠ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ رِزۡقٞ مَّعۡلُومٞ ٤١ فَوَٰكِهُ وَهُم
مُّكۡرَمُونَ ٤٢ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ٤٣ عَلَىٰ سُرُرٖ مُّتَقَٰبِلِينَ ٤٤ يُطَافُ عَلَيۡهِم بِكَأۡسٖ مِّن مَّعِينِۭ ٤٥ بَيۡضَآءَ لَذَّةٖ لِّلشَّٰرِبِينَ ٤٦ لَا فِيهَا غَوۡلٞ وَلَا هُمۡ
عَنۡهَا يُنزَفُونَ ٤٧ وَعِندَهُمۡ قَٰصِرَٰتُ ٱلطَّرۡفِ عِينٞ ٤٨ كَأَنَّهُنَّ بَيۡضٞ مَّكۡنُونٞ ٤٩

38. Lalle ku tabbas za ku ɗanɗani azaba mai tsanani.

39. Ba kuwa za a saka muku ba sai da irin abin da kuka kasance kuna aikatawa.

40. Sai dai bayin Allah waɗanda aka tsarkake.

41. Waɗannan suna da arziki sananne.

42. (Shi ne) kayan marmari; su kuma ababen karramawa ne.

43. A cikin gidajen Aljanna na ni’ima.

44. A kan gadaje suna fuskantar juna.

45. Ana zagaya su da kofuna na giya.

46. Fara fat, ga kuma daɗi ga masu sha.

47. Babu sa ciwon kai a gare ta, kuma ba za a bugar da su da ita ba.

48. A wurinsu kuma akwai mataye masu taƙaita kallonsu ga mazajensu, masu ƙwala-ƙwalan ido.

49. Kai ka ce su wani ƙwai ne a cikin kwasfa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mushirikai waɗanda suka zaɓi zama cikin bautar wanin Allah da ƙaryata Manzo (ﷺ) za su ɗanɗani azaba mai raɗaɗi ranar alƙiyama sakamakon munanan ayyukansu, domin kuwa ba za a saka musu da komai ba sai da abin da suka kasance suna aikatawa a duniya na kafirci da saɓon Allah.
A ɗaya ɓangaren kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon muminai waɗanda suka tsantsanta bautarsu gare shi, kuma ya tsarkake su, to su waɗannan Allah ya tserar da su daga azaba, suna kuma da arzikinsu sananne da Allah ya tanadar musu, wanda ya ƙunshi kayan marmari iri-iri waɗanda ba su taɓa gani ko cin abu mai daɗi irinsu ba, sannan kuma a karrama su da babban matsayi a gidajensu na Aljanna, har ma a datar da su da ganin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Wannan tagomashi kuma za su same shi ne a gidajen Aljannar ni'ima madawwamiya wadda ba za ta yanke ba har abada.
Allah kuma ya ambaci wasu dangogin ni'imomin da za a tanadar musu a Aljanna. Daga ciki akwai gadaje na alfarma da za su kishingiɗa a kansu suna fuskantar junansu, watau sun yi da'ira babu wanda zai juya wa ɗan'uwansa baya suna cike da farin ciki, ana kuma zagaya su da kofuna na giya tatacciya garai-garai kamar wani idanun ruwa mai kwarara, kuma ga ta fara fat, duk wanda ya sha ta zai samu cikakken jin daɗi da annashawa, domin ita ba kamar giyar duniya ce ba, ba ta gusar da hankali ba kuma ta sanya ciwon kai, sai dai ta ƙara wa mai shan ta lafiyar hankali da ta jiki.
Sannan kuma za a ba su `yan mata kyawawa masu kamun kai waɗanda ba sa kallon wasu maza in ba nasu ba, masu kuma kyawawan idanu, ga su kuma farare ƙal, idan mutum ya kalle su zai ga kamar ƙwan tsuntsaye ne da yake cikin kwasfarsa, a killace kuma babu wani hannu da ya taɓa shafar su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cikar farin cikin 'yan Aljanna.

2. 'Yan Aljanna sukan yi hirar abubuwan da suka faru gare su a duniya. Wannan yana daga cikin kamalar jin daɗinsu.

3. Guje wa abota da lalatattun mutane domin gudun su hallaka mutum.

4. Ganin wanda yake cikin wata musiba ko azaba, zai sanya wa mutum godiyar Allah da bai saka shi cikin wannan mummunan hali ba.

5. Shiga Aljanna ni'ima ce babba da ya wajaba kowa ya yi aikin alheri tuƙuru domin dacewa da ita.

Suratus Saffat (50-61)
فَأَقۡبَلَ بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖ يَتَسَآءَلُونَ ٥٠ قَالَ قَآئِلٞ مِّنۡهُمۡ إِنِّي كَانَ لِي قَرِينٞ ٥١ يَقُولُ أَءِنَّكَ لَمِنَ ٱلۡمُصَدِّقِينَ ٥٢ أَءِذَا مِتۡنَا وَكُنَّا تُرَابٗا وَعِظَٰمًا
أَءِنَّا لَمَدِينُونَ ٥٣ قَالَ هَلۡ أَنتُم مُّطَّلِعُونَ ٥٤ فَٱطَّلَعَ فَرَءَاهُ فِي سَوَآءِ ٱلۡجَحِيمِ ٥٥ قَالَ تَٱللَّهِ إِن كِدتَّ لَتُرۡدِينِ ٥٦ وَلَوۡلَا نِعۡمَةُ رَبِّي لَكُنتُ مِنَ
ٱلۡمُحۡضَرِينَ ٥٧ أَفَمَا نَحۡنُ بِمَيِّتِينَ ٥٨ إِلَّا مَوۡتَتَنَا ٱلۡأُولَىٰ وَمَا نَحۡنُ بِمُعَذَّبِينَ ٥٩ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٦٠ لِمِثۡلِ هَٰذَا فَلۡيَعۡمَلِ ٱلۡعَٰمِلُونَ ٦١

50. Sannan sashinsu ya fuskanci shashi suna tambayar juna.

51. Wani daga cikinsu ya ce: “Lalle a da can ina da wani aboki.

52. “Da yake cewa: ‘Yanzu kai kana cikin masu ba da gaskiya?

53. “’Yanzu idan muka mutu muka zama ƙasa da ƙasusuwa shin ko za a iya yi mana wani sakamako?’”

54. Ya ce: “Shin ko za ku leƙa ne?”

55. Sai shi ya leƙa, sai kuwa ya gan shi a tsakiyar wuta.

56. Ya ce: “Wallahi ka kusa ka hallakar da ni.

57. “Ba don rahamar Ubangijina ba, da lalle ni ma na zama cikin ‘yan wuta.”

58. (Sai ‘yan Aljanna su ce da juna): “Ashe yanzu ba za mu sake mutuwa ba?

59. “Sai fa mutuwarmu ta farko, ba kuma za a azabtar da mu ba?”

60. Lalle wannan shi ne babban rabo.

61. Don samun irin wannan lalle masu (kyakkyawan) aiki su yi aiki.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci ‘yan Aljanna da cikar farin cikinsu da ni’imomin da ya ba su, sai kuma ya bayyana irin hirar da suke yi a cikin Aljanna da junansu a kan abubuwan da suka faru a rayuwarsu ta duniya, har wani daga cikinsu yake faɗa wa ‘yan’uwansa cewa, yana da wani aboki a duniya wanda bai yarda da ranar lahira ba, har ta kai yake yi wa abokinsa mumini izgili da cewa, yanzu shi yana cikin masu gaskata tashi bayan mutuwa; bayan mutane sun mutu sun zama ƙasa da ƙasusuwa rududdugaggu, kuma a ce wai za a sake tashin su da ransu a yi musu hisabi a kan ayyukansu na duniya? Yana ganin wautarsa da har ya amince da haka. Bayan wannan mumini ɗan Aljanna ya gama ba wa abokansa labarinsa shi da abokinsa mai ƙaryata tashi bayan mutuwa, sai ya nemi abokansa da su raka shi ya je ya leƙa wuta don ya ga halin da wancan kafirin abokin nasa yake ciki domin su ƙara gode wa Allah a kan ni’imar da ya yi musu. Da suka je suka leƙa wutar Jahannama sai kuwa ya tsinkayo abokin nan nasa a tsakiyar wutar Jahannama, nan take ya tuna babbar ni’imar da Allah ya yi masa da ya tsare shi, abokinsa bai ja shi zuwa kafirci ba. Ya rantse masa da Allah cewa saura ƙiris ya hallaka shi, ya sa shi ma ya kafirce wa Allah da ranar alƙiyama. Ya ƙara da cewa, ba don ni’imar da Allah Ubangijinsa ya yi masa ba, da yanzu shi ma yana cikin wuta tare da wannan aboki nasa kafiri. Don haka sai farin ciki ya ƙara rufe shi har yake faɗa wa ‘yan’uwansa ‘yan Aljanna cewa daga yanzu kam babu sauran wata mutuwa a gare su in ban da mutuwarsu ta farko da suka yi aka tashe su, ba kuma za a yi musu azaba ba, sai dai a dawwamar da su a cikin gidan Aljanna har abada. Suka tabbatar da cewa wannan sakamako da Allah ya yi musu shi ne babban rabo da babu kamarsa.
Sai kuma Allah ya kwaɗaitar da bayinsa a kan aikin alheri tuƙuru. domin samun rabo mai girma irin wannan, domin wannan shi ne kasuwanci mai cikakkiyar riba da babu tazgaro a cikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abincin ‘yan wuta shi ne `ya`yan itaciyar Zaƙkumi mai tsananin ɗaci da wari ga kuma wahalar tauna da haɗiya.

2. Mummunan sakamakon bin iyaye da kakanni a kan ɓata da ƙin gaskiya.

3. Tabbatar da sakamako ranar alƙiyama.

Suratus Saffat (62-70)

أَذَٰلِكَ خَيۡرٞ نُّزُلًا أَمۡ شَجَرَةُ ٱلزَّقُّومِ ٦٢ إِنَّا جَعَلۡنَٰهَا فِتۡنَةٗ لِّلظَّٰلِمِينَ ٦٣ إِنَّهَا شَجَرَةٞ تَخۡرُجُ فِيٓ أَصۡلِ ٱلۡجَحِيمِ ٦٤ طَلۡعُهَا كَأَنَّهُۥ رُءُوسُ ٱلشَّيَٰطِينِ ٦٥ فَإِنَّهُمۡ لَأٓكِلُونَ مِنۡهَا فَمَالِـُٔونَ مِنۡهَا ٱلۡبُطُونَ ٦٦ ثُمَّ إِنَّ لَهُمۡ عَلَيۡهَا لَشَوۡبٗا مِّنۡ حَمِيمٖ ٦٧ ثُمَّ إِنَّ مَرۡجِعَهُمۡ لَإِلَى ٱلۡجَحِيمِ ٦٨ إِنَّهُمۡ أَلۡفَوۡاْ ءَابَآءَهُمۡ ضَآلِّينَ ٦٩ فَهُمۡ عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِمۡ يُهۡرَعُونَ ٧٠

62. Shin wannan liyafa ita ce ta fi alheri ko kuwa bishiyar Zaƙkum?

63. Lalle Mu Mun sanya ta don ta zama fitina ga azzalumai.

64. Lalle ita wata bishiya ce da take fitowa a tsakiyar wutar Jahima.

65. ‘Ya’yanta kai ka ce kawunan shaiɗanu ne.

66. To su lalle za su ci daga gare ta, za su kuma cika cikkuna da ita.

67. Sannan kuma suna da wani gauraye na tafasasshen ruwa a kanta.

68. Sannan kuma lalle makomarsu wutar Jahima ce.

69. Lalle su sun sami iyayensu ɓatattu.

70. Sai suka riƙa gaggawar bin sawunsu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tambayar mutane cewa, shin waɗancan ni’imomi na gidan Aljanna da aka ambata su ne suka fi alheri da karamci ko kuma bishiyar Zaƙkumi wadda aka la’ance ta a cikin Alƙur’ani, wadda kuma ita ce abincin kafirai wanda ba ya sa ƙiba ba ya kuma maganin yunwa.
Allah ya bayyana cewa ya sanya wannan bishiyar don ta zama fitina ga kafirai azzalumai, domin lokacin da suka ji an ambaci cewa bishiya ce a tsakiyar wuta, sai suka ƙaryata hakan suka nuna cewa ai babu yadda za a yi bishiya ta tsiro a cikin wuta, domin wuta takan cinye duk wani itace da tsiro, ba zai yiwu ba kuma a ce har ya fito a cikinta.
Sai kuma ya siffanta ta da cewa wata mummunar bishiya ce wadda take fitowa a can ƙarƙashin Jahannama, kuma ‘ya’yanta ba su da kyan gani sai ka ce kawunan shaiɗanu ne. Wannan kuma yana nuna tsananin munin ɗanɗanonta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa kafirai ba makawa za su ci ‘ya’yan wannan itaciya mai matuƙar ɗaci, har sai sun cika cikkunansu da ita, sannan su bi ta da tafasasshen ruwa, kuma makomarsu bayan haka zuwa wutar Jahimu ce, inda za a riƙa kwasar su daga wannan azabar zuwa wata.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da ya jawo musu wannan mummunan hali da suka shiga, watau bin hanyar da iyayensu ɓatattu suke a kai da kauce wa hanyar shiriya, ba bisa ga wata hujja da suke da ita ba, suka bijire wa hanyar manzannin Allah da shiriyar da suka zo da ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mafiya yawan al'ummar da suka gabata ɓatattu ne ba su karɓi shiriyar da annabawansu suka zo musu da ita ba.

2. Gargaɗi da tsoratarwa ga mushirikan wannan al'umma da su guji aikata abin da zai kai su ga hallaka da mummunan ƙarshe irin yadda ya kasance ga kafiran farko.

Suratus Saffat (71-74)

وَلَقَدۡ ضَلَّ قَبۡلَهُمۡ أَكۡثَرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٧١ وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا فِيهِم مُّنذِرِينَ ٧٢ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُنذَرِينَ ٧٣ إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلۡمُخۡلَصِينَ ٧٤

71. Haƙiƙa kafin su mafi yawan mutanen farko sun ɓata.

72. Kuma haƙiƙa Mun aiko masu gargaɗi a cikinsu.

73. To ka dubi yadda ƙarshen waɗanda aka yi wa gargaɗi ya kasance.

74. Sai dai bayin Allah waɗanda aka tsarkake.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzon Allah cewa ba mutanensa ne kaɗai suka ɓace ba, yawancin al'ummun da suka gabace su sun zama ɓatattu, duk kuwa da cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika musu da manzanni masu yi musu gargaɗi suna kuma tsoratar da su azabar Allah, to amma sai suka kafirce, don haka Allah ya hallaka su. Sai Allah ya tuna wa Manzonsa (ﷺ) cewa ya duba ya ga yadda ƙarshen waɗannan mutane da aka yi wa gargaɗi suka bijire ya kasance. Ƙarshensu shi ne shiga wutar Jahannama su kuma dawwama a cikinta har abada, saboda kafircinsu da saɓon Allah da suka yi.
Sai kuma Allah ya bayyana cewa akwai kaɗan daga cikinsu waɗanda ya tsarkake su da Imani, to waɗannan zai kuɓutar da su daga mummunan ƙarshe wanda ya sami kafirai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana amsa addu'ar annabawansa da manzanninsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi kansa a kan amsa addu'o'in annabawansa da waliyyansa.

3. Zamantowar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne uban mutane na biyu, saboda bayan ruwan Ɗufana ya hallaka al'ummarsa babu wanda ya yi saura a bayan ƙasa sai zurriyarsa, su ne suka sake hayayyafar sauran mutane.

4. Sunna ce ta Allah ya wanzar wa da bayinsa nagari kyakkyawan yabo a bayansu gwargwadon yadda suka kyautata ayyukansu.

5. Imani shi ne mafi girman alhairin da bawa zai samu. Imani ya ƙunshi dukkan shari'un addini da ginshiƙansa da ayyukansa, domin da shi ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi bayinsa na musamman.

Suratus Saffat (75-82)

وَلَقَدۡ نَادَىٰنَا نُوحٞ فَلَنِعۡمَ ٱلۡمُجِيبُونَ ٧٥ وَنَجَّيۡنَٰهُ وَأَهۡلَهُۥ مِنَ ٱلۡكَرۡبِ ٱلۡعَظِيمِ ٧٦ وَجَعَلۡنَا ذُرِّيَّتَهُۥ هُمُ ٱلۡبَاقِينَ ٧٧ وَتَرَكۡنَا عَلَيۡهِ فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ٧٨
سَلَٰمٌ عَلَىٰ نُوحٖ فِي ٱلۡعَٰلَمِينَ ٧٩ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٨٠ إِنَّهُۥ مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٨١ ثُمَّ أَغۡرَقۡنَا ٱلۡأٓخَرِينَ ٨٢

75. Kuma haƙiƙa Nuhu ya roƙe Mu, to madalla da Masu amsawa.

76. Muka kuma tserar da shi tare da iyalinsa daga baƙin ciki mai girma.

77. Muka kuma sanya zuriyarsa su ne suka wanzu.

78. Muka kuma bar (kyakkyawan yabo) a gare shi ga 'yan baya.

79. Aminci ya tabbata ga Nuhu a cikin talikai.

80. Lalle Mu kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa.

81. Lalle shi yana daga bayinmu muminai.

82. Sannan Muka nutsar da sauran.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya karɓi addu’ar Annabinsa Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da ya yi wa mutanensa addu’a bayan ya shekara dubu ba hamsin a cikinsu yana yi musu wa’azi amma suka ƙaryata shi. Dalili kenan ya sa ya roƙi Allah ya hallaka su gaba ɗayansu. Bayan Allah ya karɓi addu’ar Annabi Nuhu, sai kuma ya yabi kansa da gaggauta amsa addu’ar bayinsa nagari da yake yi yayin da suka roƙe shi.
Haka kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuɓutar da Annabinsa Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da iyalan gidansa da waɗanda suka yi imani da shi daga cutarwar mutanensa, da kuma azabar nutsewa a ruwan Ɗufana wanda ya hallaka su da shi baki ɗaya. Babu wanda ya yi saura a bayan ƙasa sai zurriyarsa, ya kuma zama abin yabo a cikin al’ummun da suka zo daga baya. Sannan Allah ya tabbatar masa da aminci da kuɓuta daga duk wata mummunar magana da za a faɗa a kansa, sai dai a yi ta ambaton sa da alheri ana yabon sa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa irin wannan kyakkyawan sakamako da ya yi wa Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) irinsa ne yake yi wa bayinsa masu kyautata ibadarsu da yi masa ɗa’a. Kuma shi Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana cikin manyan bayinsa muminai masu biyayya gare shi, kuma sauran al’ummarsa gaba ɗaya da suka bijire ya nutsar da su cikin ruwan Ɗufana wanda ya aiko musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daga cikin manyan siffofin annabawa da manzannin Allah akwai kuɓutar zukatansu daga shirka da kafirci da sha’awace-sha’awace masu hana fahimtar gaskiya da aiki da ita. Idan bawa yana da lafiyayyar zuciya to sai ya kuɓuta daga duk wani sharri, ya kuma dace da kowane alheri.

2. Duk wanda yake bauta wa wani ba Allah ba, to ya nufi ƙarya ce tsantsarta, yana kuma yi wa Allah zaton tawaya da aibi tare da shi.

3. Duk wanda yake riya cewa akwai wani abin bauta ba Allah ba to babban maƙaryaci ne.

4. Halaccin yin magana mai harshen damo domin kauce wa ƙarya, kamar yadda Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi yayin da ya faɗa wa mutanensa cewa shi marar lafiya ne, watau yana nufin shi wanda zai iya rashin lafiya ne a matsayinsa na ɗan'adam ko da kuwa a lokacin lafiyarsa lau. To amma sai mutanensa suka fahimci cewa yana nufin a daidai lokacin ba shi da lafiya, don haka sai suka karɓi hanzarin da ya ba su na rashin fita tare da su.

Suratus Saffat (83-93)

*وَإِنَّ مِن شِيعَتِهِۦ لَإِبۡرَٰهِيمَ ٨٣ إِذۡ جَآءَ رَبَّهُۥ بِقَلۡبٖ سَلِيمٍ ٨٤ إِذۡ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوۡمِهِۦ مَاذَا تَعۡبُدُونَ ٨٥ أَئِفۡكًا ءَالِهَةٗ دُونَ ٱللَّهِ تُرِيدُونَ ٨٦ فَمَا ظَنُّكُم بِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٨٧ فَنَظَرَ نَظۡرَةٗ فِي ٱلنُّجُومِ ٨٨ فَقَالَ إِنِّي سَقِيمٞ ٨٩ فَتَوَلَّوۡاْ عَنۡهُ مُدۡبِرِينَ ٩٠ فَرَاغَ إِلَىٰٓ ءَالِهَتِهِمۡ فَقَالَ أَلَا تَأۡكُلُونَ ٩١ مَا لَكُمۡ لَا تَنطِقُونَ ٩٢ فَرَاغَ عَلَيۡهِمۡ ضَرۡبَۢا بِٱلۡيَمِينِ ٩٣

83. Lalle kuma Ibrahimu yana daga mabiya addininsa.

84. A yayin da ya zo wa Ubangijinsa da lafiyayyar zuciya.

85. Lokacin da ya ce da babansa da kuma mutanensa: "Me kuke bauta wa ne?

86. "Yanzu iyayen giji na ƙarya ba Allah ba kuke nufi?

87. "To mene ne tsammaninku game da Ubangijin talikai?"

88. Sai ya yi duba a cikin taurari, duba na tunani.

89. Sannan ya ce: "Lalle ni fa ba ni da lafiya."

90. Sai suka juya daga wurinsa suna masu ba da baya.

91. Sai ya saɗaɗa zuwa ga gumakansu ya ce (da su): "Yanzu ba za ku ci (abincin da ke gabanku) ba?

92. "Me ya sa ba kwa yin magana ne?"

93. Sai ya yi kansu yana duka da hannunsa na dama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa yana daga cikin mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka rungumi Tauhidi da kiran mutane zuwa ga Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tuna lokacin da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya je wa Ubangijinsa da lafiyayyar zuciya wadda babu shirka a cikinta, ya kuma zamanto mai nasiha ga mutanensa, har da mahaifinsa lokacin da ya zarge su da bautar wani ba Allah ba. Ya ƙalubalance su da cewa ta yaya za su yarda su riƙa bauta wa allolin ƙarya su bar Ubangijinsu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka)? Kuma me suke zato ne daga Allah Ubangijin talikai idan har suka haɗu da shi suna kan bauta wa wasu ba shi ba? Me suke tsammanin zai saka musu da shi?!

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga tunanin yadda zai raba mutanensa da gumakansu da suke bauta wa ba Allah ba, sai ya shirya dabarar da zai kakkarya su bayan mutanensa sun tafi wajen bukukuwansu, shi kuma ya ƙi bin su, ya nuna musu cewa ba shi da lafiya ne don haka ba zai iya fita tare da su ba. Sai suka bar shi suka juya suka tafi. Ganin wannan dama da ta samu sai Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya saɗaɗa da sauri wajen allolinsu domin ya farfasa su. Sai ya samu an ajiye musu dangogin abinci iri-iri wai don su sa musu albarka; sai ya yi musu magana cikin izgili cewa, me ya sa ba za su ci abincin da masu bautar su suka kawo musu ba? Kuma me ya sa ba sa amsa wa mai tambayar su magana? Yana nufin ta yaya za a ce waɗannan su ne ababan bauta? Daga nan sai ya yi kansu yana dukan su da hannunsa na dama domin ya kakkarya su. Ya kuwa yi rugurugu da su gaba ɗayansu sai babbansu kawai ya bari don mutanensa idan sun komo ya yi musu wa'azi da shi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ibrahimu bai taɓa yin ƙarya ba sai sau uku, biyu daga cikinsu ya yi su ne don Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a faɗarsa: "Lalle ni ba ni da lafiya;" da faɗarsa: "A'a, wannan babban nasu shi ya aikata shi." Annabi (ﷺ) ya ce: "Wata rana shi da matarsa Saratu suka je ga wani azzalumin sarki, sai aka faɗa masa cewa akwai wani mutum yana nan tare da matarsa mai matuƙar kyau. Sai ya aika aka zo da Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tambaye shi: "Wace ce wannan?" Sai ya ce: 'Yar'uwata ce.' Sai kuma ya sami matarsa Saratu ya faɗa mata cewa: 'Ya Saratu, a duk bayan ƙasa babu wani mumini daga ni sai ke, to Sarki ya tambaye ni ke wace ce, na ce masa ke 'yar'uwata ce, don haka kada ki ƙaryata ni.' Sai Sarki ya aika aka zo masa da Saratu, ya miƙa hannunsa zai taɓa ta sai hannunsa ya ƙage. Sai ya ce mata: 'Ki roƙa mini Allah, ba zan cutar da ke ba.' Sai ta roƙa masa Allah sai hannunsa ya saki, sannan ya sake miƙa hannunsa zai kama ta sai ya sake ƙagewa fiye da karon farko, sai ya nemi ta yi masa addu'a kuma ba zai cutar da ita ba, sai ta yi masa addu'a hannunsa ya saki. Daga nan sai ya kira wani dogarinsa ya ce masa: 'Lalle fa ku ba mutum kuka kawo mini ba, kawai kun kawo mini shaiɗani ne.' Sai ya ba ta kyautar Hajara don ta riƙa yi mata hidima…" [Bukhari #3358 da Muslim #2371].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda ya ƙagi halitta shi ne ya cancanta a bauta masa, ba wanda aka halitta ba, bai kuma halicci komai ba.

2. Rashin hankalin masu bautar gumaka, domin mai hankali ba zai sassaƙa wani abu da hannunsa ba sannan ya riƙa bauta masa.

3. Duk sa'adda maɓarnata suka kasa fuskantar mai faɗar gaskiya da hujja, to za su yi amfani ne da ƙarfinsu ko sa iya murƙushe gaskiya ta haka.

4. Taimakon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga annabawansa.

5. Duk wanda ya nufi cutar da mai gaskiya, to shi ne Allah zai ƙasƙanta shi ya taɓar da shi.

6. Duk wanda ya koma ga Allah to zai shiryar da shi tafarki madaidaici.

7. Wajabcin yin hijira daga garin da ake hana bautar Allah zuwa inda mutum zai bauta wa Allah ba tare da tsangwama ba.

8. Allah ya yi wa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) albishir da samun ɗa mai haƙuri lokacin da yake da tsananin buƙatar haihuwa da samun wanda zai taimaka masa wajen isar da saƙon Allah, musamman bayan rabuwarsa da mutanensa da garinsa. Don haka malamai suka ce wannan yaro da aka yi masa albishir da shi, shi ne ɗansa Isma'il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), domin shi ne ɗansa na farko.

Suratus Saffat (94-101)

فَأَقۡبَلُوٓاْ إِلَيۡهِ يَزِفُّونَ ٩٤ قَالَ أَتَعۡبُدُونَ مَا تَنۡحِتُونَ ٩٥ وَٱللَّهُ خَلَقَكُمۡ وَمَا تَعۡمَلُونَ ٩٦ قَالُواْ ٱبۡنُواْ لَهُۥ بُنۡيَٰنٗا فَأَلۡقُوهُ فِي ٱلۡجَحِيمِ ٩٧ فَأَرَادُواْ بِهِۦ كَيۡدٗا فَجَعَلۡنَٰهُمُ ٱلۡأَسۡفَلِينَ ٩٨ وَقَالَ إِنِّي ذَاهِبٌ إِلَىٰ رَبِّي سَيَهۡدِينِ ٩٩ رَبِّ هَبۡ لِي مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١٠٠ فَبَشَّرۡنَٰهُ بِغُلَٰمٍ حَلِيمٖ ١٠١

94. Sai (mutanensa) suka fuskanto shi suna gaggawa.

95. Ya ce: "Yanzu kwa riƙa bauta wa abin da kuke sassaƙawa?

96. "Alhali kuwa Allah ne Ya halicce ku, da ma abin da kuke aikatawa?"

97. Suka ce: "Ku gina masa wani gini (ku haɗa wuta a ciki), sannan ku jefa shi cikin wutar."

98. Sai suka yi nufin sa da mugun shiri, sai Muka mayar da su mafiya ƙasƙanci.

99. Ya kuma ce: "Lalle ni zan yi ƙaura zuwa ga Ubangijina, zai ko shiryar da ni.

100. "Ya Ubangijina, Ka yi min baiwa da (ɗa) ya zama daga (mutane) nagari."

101. Sai Muka yi masa albishir da yaro mai haƙuri.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mutanen Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ɗawo zuwa wurin gumakansu da gaggawa inda suka sami Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi guntu-guntu da gumakansu, sai suka fara zargin sa da aikata wani babban laifi, sai shi kuma ya fuskance su yana kushe wa mummunar aƙidarsu ta bautar gumaka, yana nuna musu wautarsu da har suke bauta wa abubuwan da su ne suka sassaƙa su da hannayensu su bar bautar Allah wanda shi ne ya halicce su har da duk aikin da suke yi, daga ciki har da sassaƙa gumakansu duk halittar Allah ne shi kaɗai, don haka shi ya cancanta su bauta wa kada su haɗa komai da shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa lokacin da mutanensa suka kasa fuskantar sa da wata ƙwaƙƙwarar hujja ta bautar wasu ba Allah ba, sai suka ga gara su ɗauki mataki na amfani da ƙarfi, sai suka yi shawara game da matakin da ya kamata su ɗauka a kan Annabi Ibrahim. A ƙarshe suka yanke shawarar su yi wani gini wanda za su hura wuta a cikinsa sai su jefa shi ciki ya ƙone ƙurmus kowa ya huta. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kunyata su inda ya ce, mutanen Annabi Ibrahim sun shirya masa mummunan makirci don su hallaka shi su huta da shi, to amma sai Allah ya mayar da su su ne taɓaɓɓu waɗanda suka yi hasara duniya da lahira, domin kuwa da suka jefa shi cikin wutar sai ta zama sanyi da aminci a gare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yanke shawarar cewa shi zai yi hijira zuwa ga Ubangijinsa, ya bar garinsa da mutanensa domin ya sami damar bautar Allah cikin kwanciyar hankali, ya kuma sakankance cewa Ubangijinsa zai nuna masa alherin duniya da lahira.
Sai kuma ya roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya arzuta shi da samun ɗa nagari wanda zai zama mai taimakon sa kuma ya zamanto madadin mutanensa da ya bari ya tafi bakunta wani gari.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya karɓi addu’arsa ya kuma yi masa albishir da samun ɗa wanda za a haifa masa shi kuma ya girma ya zama mai haƙuri da juriya. Wannan ɗa kuwa shi ne Isma’il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An nuna wanda Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi niyyar yankawa daga cikin `ya`yansa, shi ne babban ɗansa Annabi Isma’il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) saboda dalilai masu zuwa:
Na ɗaya, albishir na farko da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara yi wa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba shi ne na biyu ba. Domin ba zai yiwu ba a ce Allah ya yi masa albishir ɗin farko yana nufin Ishaƙ, sannan kuma ya ambaci ƙissar yanka shi, sannan ya sake cewa mun yi masa albishir da Ishaƙ, domin yin haka maimai ne marar amfani wanda bai dace da maganar Allah ba. Don haka albishir na farko daban yake da albishir na biyu wanda aka ambaci sunan Ishaƙ a cikinsa. Na farkon Annabi Isma’ila ake nufi.
Na biyu, a cikin *Suratu Hud* aya ta 71 mala’iku sun yi wa Saratu albishir da samun ɗa Ishaƙa da kuma cewa, shi kuma zai haifi ɗansa Ya’aƙub; to ta yaya za a dawo a umarce shi da ya yanka shi tun yana matashi bayan an riga an tabbatar masa da cewa zai rayu har ya girma ya haifi ɗa Ya’aƙub?
Na uku, a duk cikin Alƙur'ani inda ya tabbata cewa Ishaƙ ne aka ambata to an siffanta shi ne da ilimi ba da haƙuri ba. Amma wannan yaron da aka umarci a yanka shi an siffanta shi ne da haƙuri, sai wannan ya tabbatar da cewa ba Ishaƙ ake nufi ba.
Na huɗu, Isma’ila ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta da haƙuri ba Ishaƙ ba, kamar yadda ya zo a cikin *Suratul Anbiya* aya ta 85. Babu shakka haƙurin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabe shi da shi haƙuri ne mai girma sosai, shi ne wannan da ya zo a wannan ƙissar.
Na biyar, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci cewa ya yi wa Ibrahim albishir da Ishaƙ wanda zai zama annabi. To ba zai yiwu ya yi masa albishir da zamantowarsa annabi ba sannan kuma ya umarce shi ya yanka shi yana yaro.

2. Jarrabar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi wa annabawansa babba ce fiye da sauran bayinsa nagari, don ya ɗaukaka darajarsu.

3. Mafarkin annabawa dukkansa gaskiya ne. Duk wanda ba annabi ba mafarkinsa zai iya zama gaskiya zai kuma iya zama ba gaskiya ba, sai dai mafi yawancin mafarkin masu gaskiya yakan zama gaskiya ne.

4. Tsananin biyayyar Isma’il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ga mahaifinsa.

5. Karami yana iya kwaɗaitar da babba a kan aikata alheri: yin haka ba rashin ladabi ne ba.

6. Duk abin da mutum zai aikata a nan gaba yana da kyau matuƙa ya danganta shi da izinin Allah da yardarsa, domin komai yana ƙarƙashin ikonsa ne (Mai tsarki da ɗaukaka).

7. Nasara tana tare da haƙuri.

8. Duk wani mai kyautatawa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yaye masa damuwarsa, yana kuma ba shi ladan duk ibadar da ya yunƙura zai aikata amma wani abu ya hana shi aikata ta.

9. Kiran mutum ‘bawan Allah’ siffa ce mai girman gaske, shi ya sa Allah ya siffanta manyan annabawansa da ita.

10. Ba lalle ne zurriyar wani bawan Allah nagari dukkansu su zamanto nagartattu kamarsa ba.

Suratus Saffat (102-113)

فَلَمَّا بَلَغَ مَعَهُ ٱلسَّعۡيَ قَالَ يَٰبُنَيَّ إِنِّيٓ أَرَىٰ فِي ٱلۡمَنَامِ أَنِّيٓ أَذۡبَحُكَ فَٱنظُرۡ مَاذَا تَرَىٰۚ قَالَ يَٰٓأَبَتِ ٱفۡعَلۡ مَا تُؤۡمَرُۖ سَتَجِدُنِيٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٠٢ فَلَمَّآ أَسۡلَمَا وَتَلَّهُۥ لِلۡجَبِينِ ١٠٣ وَنَٰدَيۡنَٰهُ أَن يَٰٓإِبۡرَٰهِيمُ ١٠٤ قَدۡ صَدَّقۡتَ ٱلرُّءۡيَآۚ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٠٥ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ ٱلۡبَلَٰٓؤُاْ ٱلۡمُبِينُ ١٠٦ وَفَدَيۡنَٰهُ بِذِبۡحٍ عَظِيمٖ ١٠٧ وَتَرَكۡنَا عَلَيۡهِ فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ١٠٨ سَلَٰمٌ عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ ١٠٩ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١١٠ إِنَّهُۥ مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١١١ وَبَشَّرۡنَٰهُ بِإِسۡحَٰقَ نَبِيّٗا مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١١٢ وَبَٰرَكۡنَا عَلَيۡهِ وَعَلَىٰٓ إِسۡحَٰقَۚ وَمِن ذُرِّيَّتِهِمَا مُحۡسِنٞ وَظَالِمٞ لِّنَفۡسِهِۦ مُبِينٞ ١١٣

102. To lokacin da ya kai matsayin yin aiki tare da shi, sai ya ce: “Ya kai ɗana, lalle na ga ina yanka ka a cikin mafarki, sai ka yi tunani me ka gani?” Sai ya ce: “Ya babana, ka aikata duk abin da aka umarce ka, za ka same ni insha Allahu daga cikin masu haƙuri.”

103. To lokacin da suka sallama wa (Allah), ya kuma kwantar da shi ta ɗaya gefe na goshinsa (da nufin ya yanka shi).

104. Sai Muka kira shi da cewa: “Ya Ibrahimu.

105. “Haƙiƙa ka gaskata mafarkin.” Lalle Mu kamar haka ne Muke saka wa masu kyautatawa.

106. Lalle wannan tabbas shi ne bala’i ƙarara.

107. Muka kuma fanshe shi da abin yankawa mai girma.

108. Muka kuma bar (kyakkyawan yabo) a gare shi ga 'yan baya.

109. Aminci ya tabbata ga Ibrahimu.

110. Kamar haka ne Muke saka wa masu kyautatawa.

111. Lalle shi yana daga cikin bayinmu muminai.

112. Muka kuma yi masa albishir da Is’haƙa a matsayin Annabi daga salihai.

113. Muka kuma yi masa albarka, da kuma Is’haƙa. Daga zuriyarsu kuma akwai mai kyautatawa akwai kuma mai zaluntar kansa a fili (wato kafiri).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lokacin da Isma’il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya girma ya fara fita aiki tare da mahaifinsa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai mahaifin nasa ya yi wani mafarki cewa ya ga yana yanka ɗansa. Mafarkin annabawa kuwa gaskiya ne. Da ya gaya wa ɗansa wannan mafarki, ya kuma nemi ɗansa ya duba ya yi tunani game da wannan mafarki. Sai Isma’ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya amsa wa mahaifinsa cewa ya aikata duk abin da Allah ya umarce shi da shi, kuma zai same shi cikin masu haƙuri da yarda da hukuncin Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yayin da Annabi Ibrahim da ɗansa suka miƙa wuya ga hukuncin Allah suka sallama masa, sai Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kwantar da ɗansa Isma’il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a gefen goshinsa don ya cika umarnin Allah ya yanka

shi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira shi da sunansa Ibrahim, ya tabbatar masa cewa, lalle shi ya gaskata mafarkin da ya yi tunda ga shi yana ƙoƙarin yanka ɗansa, Allah ya yaba masa da karɓar jarrabawar da ya yi masa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lalle wannan jarrabawar wani bala'i ne a fili, kuma Annabi Ibrahim ya yi nasarar cinye wannan jarrabawar. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fanshi Isma'il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da wani rago babba wanda Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yanka a madadinsa.
Allah kuma ya wanzar da kyakkyawan yabo ga Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a cikin al'ummun da suka zo bayansa, ya kuma tabbatar masa da aminci da kuɓuta daga duk wani sharri ko abin ƙi, ya nuna cewa kamar yadda ya yi wa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) irin wannan sakamako to hakanan yake saka wa duk wasu masu kyautatawa, domin Annabi Ibrahim lalle ya kasance daga bayin Allah muminai masu cika bautarsu ga Allah da yi masa biyayya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Ibrahim albishir da samun wani ɗan, shi ne Is'haƙ wanda shi ma zai zama Annabi kuma bawa nagari, sakamakon biyayyar da ya yi wa Allah game da yarda ya yanka ɗansa ɗaya a lokacin, watau Isma'il (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya yi wa Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ɗansa Is'haƙa albarka daga gare shi, ya yawaita musu ni'imominsa, daga cikinsu akwai yawan 'ya'ya da ya ba su waɗanda a cikinsu akwai masu kyautatawa masu bin Allah, akwai kuma masu zaluntar kansu da kafirci da saɓon Allah da kuma bayyana zaluncinsu a fili.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babbar baiwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Musa da Haruna ita ce ta annabta, domin ita ce mafi girman daraja da Allah yake ba wa bawansa.

2. Yiwuwar aiko fiye da manzo ɗaya a lokaci guda, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko Musa da ɗan'uwansa Haruna zuwa ga Fir'auna.

3. Zama a ƙarƙashin ƙangin bauta ga wasu ko wani babban abin baƙin ciki ne. Don haka ni'ima ce mai girma Allah ya fitar da bawa daga bautar waninsa zuwa bautar Allah shi kaɗai.

4. Samun kyakkyawan yabo yana daga cikin sakamakon da Allah yake gaggauto wa bawansa mumini da shi tun a nan duniya.

Suratus Saffat (114-122)
وَلَقَدۡ مَنَنَّا عَلَىٰ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ١١٤ وَنَجَّيۡنَٰهُمَا وَقَوۡمَهُمَا مِنَ ٱلۡكَرۡبِ ٱلۡعَظِيمِ ١١٥ وَنَصَرۡنَٰهُمۡ فَكَانُواْ هُمُ ٱلۡغَٰلِبِينَ ١١٦ وَءَاتَيۡنَٰهُمَا ٱلۡكِتَٰبَ ٱلۡمُسۡتَبِينَ ١١٧ وَهَدَيۡنَٰهُمَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلۡمُسۡتَقِيمَ ١١٨ وَتَرَكۡنَا عَلَيۡهِمَا فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ١١٩ سَلَٰمٌ عَلَىٰ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ١٢٠ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٢١ إِنَّهُمَا مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٢٢

114. Haƙiƙa kuma Mun yi ni'ima ga Musa da Haruna.

115. Muka kuma tserar da su da mutanensu daga babban baƙin ciki.

116. Muka kuma taimake su, sai suka kasance su ne masu rinjaye.

117. Muka kuma ba su Littafi mabayyani (Attaura).

118. Muka kuma shiryar da su hanya madaidaiciya.

119. Muka kuma bar (kyakkyawan yabo) a gare su ga 'yan baya.

120. Aminci ya tabbata ga Musa da Haruna.

121. Lalle Mu kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa.

122. Lalle suna daga cikin bayinmu muminai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana babbar baiwar da ya yi wa Annabi Musa da ɗan'uwansa Haruna . domin ya ba su annabta, ya kuma tserar da su da mutanensu Banu Isra'ila daga ƙangin bauta a hannun Fir'auna da jama'arsa. Ya kuma kuɓutar da su daga nutsewa a cikin ruwa, a ƙarshe ya ba su nasara a kan maƙiyansu Fir'auna da rundunarsa. Ya kuma ba wa Annabi Musa da ɗan'uwansa Haruna littafin Attaura bayyananne da babu rikitarwa a cikinsa, Allah kuma ya shiryar da su tafarki madaidaici wanda babu karkata a tare da shi, shi ne addinin Musulunci mai kai wa zuwa ga samun yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya kuma wanzar musu da kyakkyawan yabo a cikin al'ummun da suka zo a bayansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa aminci ya tabbata ga Annabi Musa da ɗan'uwansa Haruna . Kuma kamar yadda Allah ya kyautata sakamako gare su saboda su ma sun kyautata, to hakanan yake saka wa bayinsa nagari masu biyayya ga Allah da kyautata wa bayinsa. Sannan ya tabbatar da cewa Annabi Musa da Haruna suna cikin bayinsa muminai masu aiki da shari'arsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da manzancin Annabi Iliyasu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda yana daga cikin annabawan Banu Isra'ila waɗanda suka yi aiki da Attaura ta Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aike shi zuwa ga sarakunan Banu Isra'ila waɗanda suka saki bautar Allah suka koma bautar wani gunki da suke kira da suna *Ba'alu*.

2. Tabbatar da cewa wanda ya ƙagi halitta ya kuma kyautata abin da ya halitta, watau Allah, shi ne ya cancanta a bauta wa ba wani abu da wani ne ya sassaƙa shi ko ya gina shi da hannunsa ba.

3. Ba dole ne duk sanda mai wa'azi ya yi wa'azinsa ya yi tasiri ba, sai Allah ya ga dama, don haka shiriya tana hannun Allah ne shi kaɗai.

4. Duk wanda ya kyautata alaƙarsa da Allah ya kuma kyautata wa bayin Allah, to Allah zai yi masa sakayya gwargwadon aikinsa, zai kuma wanzar masa da kyakkyawan yabo a bayansa.

Suratus Saffat (123-132)
وَإِنَّ إِلْيَاسَ لَمِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ﴿١٢٣﴾ إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ أَلَا تَتَّقُونَ﴿١٢٤﴾ أَتَدْعُونَ بَعْلًا وَتَذَرُونَ أَحْسَنَ ٱلْخَٰلِقِينَ﴿١٢٥﴾ ٱللَّهَ رَبَّكُمْ وَرَبَّ ءَابَآئِكُمُ ٱلْأَوَّلِينَ﴿١٢٦﴾ فَكَذَّبُوهُ فَإِنَّهُمْ لَمُحْضَرُونَ﴿١٢٧﴾ إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلْمُخْلَصِينَ﴿١٢٨﴾ وَتَرَكْنَا عَلَيْهِ فِى ٱلْءَاخِرِينَ﴿١٢٩﴾ سَلَٰمٌ عَلَىٰٓ إِلْ يَاسِينَ﴿١٣٠﴾ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِى ٱلْمُحْسِنِينَ﴿١٣١﴾ إِنَّهُۥ مِنْ عِبَادِنَا ٱلْمُؤْمِنِينَ﴿١٣٢﴾

123. Kuma lalle Ilyasu tabbas yana daga cikin manzanni.

124. Lokacin da ya ce da mutanensa: “Yanzu ba za ku kiyaye dokokin (Allah) ba?

125. “Yanzu kwa riƙa bauta wa (gunkin*) Ba’alu* ku riƙa barin Mafi iya kyautata halitta?

126. “(Wato) Allah Ubangijinku kuma Ubangijin iyayenku na farko?”

127. Sai suka ƙaryata shi, to don haka, lalle za a halarto da su (wuta).

128. Sai dai bayin Allah waɗanda aka tsarkake.

129. Muka kuma bar (kyakkyawan yabo) a gare shi ga 'yan baya.

130. Aminci ya tabbata ga Ilyasu.

131. Lalle Mu kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa.

132. Lalle shi yana daga bayinmu muminai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin cewa Annabi Iliyasu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana daga cikin manzanninsa da ya ni’imta da annabta da kuma manzanci, lokacin da ya aika shi zuwa ga mutanensa Banu Isra’ila, don ya gargaɗe su a kan su kiyaye dokokin Allah su bi umarninsa su guji haninsa, su kuma rungumi Tauhidi su guje wa shirka. Ya zarge su da cewa yanzu sa riƙa bauta wa gunkin *Ba’alu*, su yi watsi da bautar mahaliccinsu wanda ya fi kowa kyautata halitta, watau Allah wanda shi ne Ubangijin da ya halicce su ya halicci iyayensu, shi ne kuma kaɗai wanda ya cancanci a bauta masa ba gumakan da ba sa amfanarwa ba sa kuma cutarwa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mutanensa ba su yi wata-wata ba sai suka ƙaryata shi, a dalilin haka suka zamanto waɗanda za a tattara su a wuta don yi musu azaba. Amma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya togace bayinsa daga cikinsu waɗanda aka tsarkake su daga bautar wani ba Allah ba. Ya kuma wanzar wa da Annabi Iliyasu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kyakkyawan yabo a cikin al’ummun da suka zo bayansa. Amincin Allah da yabonsa kuma su tabbata ga Annabinsa Iliyasu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kamar yadda ya saka wa Annabi Iliyasu to hakanan zai yi kyakkyawan sakamakonsa ga bayinsa muminai masu kyautatawa. Ya kuma shaide shi da cewa lalle yana cikin bayinsa muminai na gaskiya masu tsoron Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da manzancin Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Taimakon Allah ga bayinsa nagari da kuma mummunan ƙarshe ga masu aikata miyagun ayyuka.

3. Kusancin mutum ga mutumin kirki ko da kuwa annabin Allah ne, ba zai amfanar da wanda bai yi imani ya yi aiki nagari ba a wurin Allah.

4. Wajibi ne mutane su riƙa ɗaukar darasi da izina daga al’ummun da suka yi mummunan ƙarshe saboda kafirci da saɓon Allah.

Suratus Saffat (133-138)

وَإِنَّ لُوطًا لَّمِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٣٣﴾ إِذْ نَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥٓ أَجْمَعِينَ ﴿١٣٤﴾ إِلَّا عَجُوزًا فِى ٱلْغَٰبِرِينَ ﴿١٣٥﴾ ثُمَّ دَمَّرْنَا ٱلْءَاخَرِينَ ﴿١٣٦﴾ وَإِنَّكُمْ لَتَمُرُّونَ عَلَيْهِم مُّصْبِحِينَ ﴿١٣٧﴾ وَبِٱلَّيْلِ ۗ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ﴿١٣٨﴾

133. Lalle kuma Luɗu tabbas yana daga cikin manzanni.

134. (Ka tuna) sanda Muka tserar da shi tare da iyalinsa baki ɗaya.

135. Sai dai wata tsohuwa (wato matarsa) da take cikin halakakku.

136. Sannan Muka hallakar da sauran.

137. Kuma lalle ku tabbas kuna wucewa ta wajan (gidajensu) da asussuba.

138. Da kuma cikin dare. Yanzu ba kwa hankalta ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ɗaya ne daga cikin manzannin da ya aika ga mutanensa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika shi zuwa ga mutanen Sadum waɗanda suka yi ƙaurin suna wajen neman maza da aikata miyagun ayyuka tare da yin shirka da Allah. Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gargaɗe su ya yi musu wa'azi amma ba su ɗauka ba, sai Allah ya aiko musu da azabarsa ta hallaka su, ya kuma tserar da Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da iyalansa in ban da wata tsohuwa, watau matarsa wadda azabar Allah ta ritsa da ita tare da mutanensa, saboda kafircinta da bijire wa gargaɗin mijinta Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jawo hankalin mutanen Makka waɗanda suke wucewa ta gaban gidajen waɗannan mutane da ya hallaka safe da yamma lokacin tafiye-tafiyensu zuwa Sham, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gaya musu cewa, me ya sa ba za su hankalta ba, su ɗauki izina daga mummunan makomar masu ƙaryata Allah da manzanninsa da dogewa a kan kafirci da saɓon Allah?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da manzancin Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Halaccin yin ƙuri'a a shari'a a kan abin da ake taƙaddama a kansa, aka kuma kasa tantance wanda ya fi cancantar sa.

3. Yayin da abubuwa biyu masu cutarwa suka haɗu, kuma babu hanyar kauce musu gaba ɗayansu, to akan ɗauki wanda ya fi sauƙin cutarwa, domin a kauce wa mafi tsanani.

4. Zaman Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a cikin cikin kifi ba tare da ya kakkarya shi ba lokacin haɗiyarsa, ko ya narke a cikinsa, ko ya mutu saboda zafin cikin kifin, wannan duka mu'ujiza ce ga Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

5. Annabawa sukan aikata wani abu da za a zarge su a kansa, to amma Allah ba ya barin su su doge a kansa, yakan nuna musu daidai domin su koma kansa ya kuma yafe musu kuskurensu.

6. Kyawawan ayyukan mutum da suka gabata sukan zama sanadiyyar kuɓutarsa daga wata hallaka ko tsame shi daga wata wahala.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da mutanen Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga hallakarwa, ya jiyar da su daɗi har zuwa ƙarshen ajalinsu.

Suratus Saffat (139-148)

وَإِنَّ يُونُسَ لَمِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ ﴿١٣٩﴾ إِذْ أَبَقَ إِلَى ٱلْفُلْكِ ٱلْمَشْحُونِ ﴿١٤٠﴾ فَسَاهَمَ فَكَانَ مِنَ ٱلْمُدْحَضِينَ ﴿١٤١﴾ فَٱلْتَقَمَهُ ٱلْحُوتُ وَهُوَ مُلِيمٌ ﴿١٤٢﴾ فَلَوْلَآ أَنَّهُۥ كَانَ مِنَ ٱلْمُسَبِّحِينَ ﴿١٤٣﴾ لَلَبِثَ فِى بَطْنِهِۦٓ إِلَىٰ يَوْمِ يُبْعَثُونَ ﴿١٤٤﴾ ۞ فَنَبَذْنَٰهُ بِٱلْعَرَآءِ وَهُوَ سَقِيمٌ ﴿١٤٥﴾ وَأَنۢبَتْنَا عَلَيْهِ شَجَرَةً مِّن يَقْطِينٍ ﴿١٤٦﴾ وَأَرْسَلْنَٰهُ إِلَىٰ مِاْئَةِ أَلْفٍ أَوْ يَزِيدُونَ ﴿١٤٧﴾ فَـَٔامَنُوا۟ فَمَتَّعْنَٰهُمْ إِلَىٰ حِينٍ ﴿١٤٨﴾

139. Kuma lalle Yunusa tabbas yana daga cikin manzanni.

140. (Ka tuna) lokacin da ya gudu zuwa ga jirgin ruwan da yake maƙare.

141. Sannan ya shiga ƙuri'a, sai ya zama cikin waɗanda aka yi galaba a kansu.

142. Sai kifi ya haɗiye shi, alhali yana abin zargi.

143. Ba don dai shi ya zama daga masu tsarkake Allah (da yawan tasbihi) ba.

144. Tabbas da ya zauna a cikin cikinsa har zuwa ranar da za a tashe su.

145. Sai Muka jefa shi a tudu, a halin yana cikin rashin lafiya.

146. Muka kuma tsirar masa wata bishiya ta kabewa.

147. Muka kuma aika shi zuwa ga mutum dubu ɗari, ko kuma sama da haka.

148. Sai suka yi imani, sai Muka jiyar da su daɗi har zuwa wani lokaci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tabbatar da cewa shi ma ɗaya ne daga cikin manzanninsa.
Amma kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci irin uƙubar da ya yi masa sannan ya kuɓutar da shi daga gare ta saboda imaninsa da kyawawan ayyukansa. Laifinsa shi ne ya gudu ya bar mutanensa waɗanda suka yi imani da shi bayan ya yi musu wa'azi. Ya je ya shiga cikin wani jirgin ruwan da yake maƙare da mutane da kayayyaki. Sai jirgin ruwan nan ya tasam ma nutsewa a ruwa saboda ya yi cikar da ta fi ƙarfinsa, sai mutanen cikinsa suka yi ƙuri'a, domin su jefa ɗaya daga cikinsu cikin ruwa su rage wa jirgin nauyi, don kauce wa nutsewar jirgin su hallaka gaba ɗaya a ruwa, sai ko ƙuri'ar ta faɗa a kan Annabi Yunusa sai suka jefa shi cikin ruwa. Jefa shi ruwa ke da wuya sai kifi ya haɗiye shi, domin ya aikata abin da za a zarge shi da shi, watau gudowa ya bar mutanensa ba tare da izinin Allah Ubangijinsa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba don Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana cikin mutane masu yawan tasbihi da tsarkake Ubangiji kafin faruwar haka ba, da kuma lokacin zamansa a cikin cikin kifi, to da ya yi ta zama cikin cikin kifin har zuwa ranar alƙiyama, domin zai zama shi ne ƙabarinsa; to amma saboda tasbihinsa da bautarsa ga Allah sai Allah ya tserar da shi daga wannan uƙuba ta duniya.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya jefo shi daga cikin kifi zuwa tsandaurin ƙasa wanda babu tsirrai a kansa, alhali yana cikin rashin lafiya saboda zamansa a cikin wannan kifin.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsirar masa da bishiyar kabewa domin ya rufe tsiraicinsa da ganyenta, ya kuma ci ‘ya’yanta, ya kuma sha inuwarta.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Wani maɗinki ya yi abinci ya gayyaci Manzon Allah (ﷺ) sai na bi shi. Sai ya kawo wa Manzon Allah (ﷺ) gurasa da romo da ke da kabewa a cikinsa, sai na ga Manzon Allah (ﷺ) yana bibiyar gefe-gefen akushin abincin yana tsintar kabewar da ke ciki, tun daga wannan ranar na ji ina son kabewa.” [Bukhari #2092 da Muslim #2041].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya sake aika Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa mutanensa su dubu ɗari ko ma sun fi haka, sai suka yi imani suka ba da gaskiya da abin da ya zo musu da shi, sai Allah ya ƙyale su suka ci gaba da jin daɗin rayuwarsu har zuwa lokacin ajalinsu da ya iyakance musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya zo da wata da’awa, to za a nemi ya kawo hujja a kanta, idan kuwa ya gaza to da’awarsa ta banza ce.

2. Mushirikai sun yi wa Allah ƙarairayi da dama, daga cikinsu akwai da’awar cewa Allah yana da ‘ya’ya mata. Duk kuwa wanda ya danganta wa Allah ɗa, to wannan maƙaryaci ne.

3. Rashin adalcin kafirai da rashin ganin girman Allah a tare da su, su suka sa suke guje wa ‘ya’ya mata amma kuma suna danganta su da Allah.

4. Duk mutumin da zai zo da wata da’awa amma ya kasa kawo dalilinta, to ya tabbata maƙaryaci ko mai danganta wa Allah magana ba da ilimi ba.

Suratus Saffat (149-160)
فَٱسۡتَفۡتِهِمۡ أَلِرَبِّكَ ٱلۡبَنَاتُ وَلَهُمُ ٱلۡبَنُونَ ١٤٩ أَمۡ خَلَقۡنَا ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ إِنَٰثٗا وَهُمۡ شَٰهِدُونَ ١٥٠ أَلَآ إِنَّهُم مِّنۡ إِفۡكِهِمۡ لَيَقُولُونَ ١٥١ وَلَدَ ٱللَّهُ وَإِنَّهُمۡ
لَكَٰذِبُونَ ١٥٢ أَصۡطَفَى ٱلۡبَنَاتِ عَلَى ٱلۡبَنِينَ ١٥٣ مَا لَكُمۡ كَيۡفَ تَحۡكُمُونَ ١٥٤ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ١٥٥ أَمۡ لَكُمۡ سُلۡطَٰنٞ مُّبِينٞ ١٥٦ فَأۡتُواْ بِكِتَٰبِكُمۡ إِن
كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ١٥٧ وَجَعَلُواْ بَيۡنَهُۥ وَبَيۡنَ ٱلۡجِنَّةِ نَسَبٗاۚ وَلَقَدۡ عَلِمَتِ ٱلۡجِنَّةُ إِنَّهُمۡ لَمُحۡضَرُونَ ١٥٨ سُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يَصِفُونَ ١٥٩ إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ
ٱلۡمُخۡلَصِينَ ١٦٠

149. Ka tambaye su: Yanzu Ubangijinka ne Yake da ‘ya’ya mata, su kuma suna da ‘ya’ya maza?

150. Ko kuma Mun halicci mala’iku ne ‘ya’ya mata a gaban idonsu suna gani?

151. Ku saurara! Lalle su saboda ƙaryarsu har suna cewa:

152. “Allah Ya haihu!” Lalle kuwa su tabbas maƙaryata ne.

153. Yanzu Ya zaɓi ‘ya’ya mata a kan ‘ya’ya maza?

154. Me ya same ku, ƙaƙa kuke yin irin wannan hukunci?

155. Me ya sa ne ba kwa wa'azantuwa?

156. Ko kuwa kuna da wata hujja ne bayyananniya?

157. To ku kawo rubutaccen littafinku idan kun kasance masu gaskiya.

158. Suka kuma sanya dangantakar nasaba tsakaninsa da mala'iku. Lalle kuwa su mala'iku sun san cewa tabbas su (masu wannan da'awar) za a kawo su (cikin wuta).

159. Tsarki ya tabbata ga Allah daga abin da suke siffanta (Shi da shi).

160. Sai dai bayin Allah waɗanda aka tsarkake.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tambayi mushirikai masu cewa mala'iku mata ne kuma 'ya'yan Allah ne cewa, yanzu sa zaɓa wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) 'ya'ya mata su kuma su zaɓa wa kansu 'ya'ya maza tare da cewa suna fifita 'ya'ya maza a kan 'ya'ya mata? Wane irin rabo ne na zalunci suke yi haka? Kuma da suke cewa mala'iku mata ne, to shin suna nan ne lokacin da Allah ya halicci mala'ikun har suka tabbatar da cewa mata ne? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa wannan shaci-faɗi ne kawai da ƙarya suke yi. Kuma jingina wa Allah ɗa ba komai ba ne sai ƙagensu da ƙaryar da suke yi masa. Ba shakka sun tabbata manyan maƙaryata.
Kuma wane irin hukunci ne a ce shi Allah ya zaɓa wa kansa 'ya'ya mata waɗanda su suke ganin nakasa ne a gare su, ya bar 'ya'ya maza waɗanda su suke ganin su kamala ne a gare su? Allah ya tambaye su cewa me ya sa suke irin wannan ɗanyen hukunci wanda sun tabbatar a riyawarsu cewa babu adalci a cikinsa?
Ya kuma nuna musu cewa, da tun farko sun tsaya sun yi tunani da sun gane ɓarnar da suke a kai da muguwar aƙidar da suka runguma. To me ya hana su yin tunani ne? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa soki-burutsu ne kawai suke yi, don ba su da wata rubutacciyar hujja daga Allah a kan abin da suke da'awa. Idan kuwa har suna ganin akwai ta to sai su kawo littafin da ya nuna hakan idan sun kasance suna da gaskiya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, mushirikai sun sanya wata dangantaka ta nasaba tsakanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da mala'iku waɗanda suke ɓoye ba a ganin su, suka ce wai 'ya'yan Allah ne mata, alhali su mala'ikun sun san cewa sai Allah ya titse masu wannan da'awar ya yi musu hisabi a kanta.
Wasu malaman tafsiri sun fassara wannan ayar da cewa, mushirikai sun sanya wata dangantaka tsakanin Allah da aljannu, yayin da suka yi da'awar cewa ya yi aure daga cikin aljannu, ta nan kuma ne wai ya samu 'ya'ya mata, watau su ne mala'iku. Sai Allah ya tabbatar musu da cewa, su waɗannan aljannu da ake ƙaryar danganta alaƙar aure da su sun san cewa waɗannan maƙaryatan tabbas sai an halarto da su zuwa ga azabar Allah, saboda girman laifinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkake kansa daga duk wani abu na shirka da mushirikai suke danganta shi da shi, kamar 'ya'ya da abokan tarayya. Ya kuma yabi bayinsa waɗanda aka tsarkake su daga aikata duk wata shirka, sun kuma kasance bayi nagari masu tsarkake Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mushirikai masu bautar wanin Allah ba za su iya ɓatar da wani da Allah ya shiryar ba, sai wanda Allah ya riga ya ƙaddara masa hallaka, to wannan da man shi ma ɓatacce ne ɗan'uwansu.

2. Mala’iku bayin Allah ne masu bauta masa da yi masa ɗa’a koyaushe, ba sa saɓa masa daidai da ƙiftawar ido.

3. Kowane mala’ika akwai inda Allah ya tsayar da shi da aikin da ya ɗora shi a kansa, wannan shi ne bautarsa ga Allah, ba ya ƙetare shi zuwa wani abu daban.

4. Mala’iku suna bautar Allah ne cikin tsari cikakke, don haka su ma muminai aka umarce su da su tsaya lokacin sallolinsu cikin sahu bisa cikakken tsari.

5. Yana daga cikin ibadar mala’iku yawan tasbihi ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) domin su tsarkake shi daga dukkan tawaya da aibu.

Suratus Saffat (161-170)
فَإِنَّكُمۡ وَمَا تَعۡبُدُونَ ١٦١ مَآ أَنتُمۡ عَلَيۡهِ بِفَٰتِنِينَ ١٦٢ إِلَّا مَنۡ هُوَ صَالِ ٱلۡجَحِيمِ ١٦٣ وَمَا مِنَّآ إِلَّا لَهُۥ مَقَامٞ مَّعۡلُومٞ ١٦٤ وَإِنَّا لَنَحۡنُ ٱلصَّآفُّونَ ١٦٥ وَإِنَّا لَنَحۡنُ ٱلۡمُسَبِّحُونَ ١٦٦ وَإِن كَانُواْ لَيَقُولُونَ ١٦٧ لَوۡ أَنَّ عِندَنَا ذِكۡرٗا مِّنَ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٦٨ لَكُنَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلۡمُخۡلَصِينَ ١٦٩ فَكَفَرُواْ بِهِۦۖ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ١٧٠

161. Lalle ku da abin da kuke bauta wa.

162. Ba za ku iya ɓatar da kowa da shi ba.

163. Sai dai wanda zai shiga wutar Jahima.

164. (Jibrilu ya ce da Mala’iku): “Ba ɗai daga cikinmu face yana da wani matsayi sananne.

165. “Lalle kuma mu masu yin sahu ne.

166. “Kuma lalle mu masu yin tasbihi ne.”

167. Kuma lalle su (kafirai) sun kasance suna cewa:

168. “Da muna da wani littafi irin na mutanen farko.

169. “Tabbas da mun kasance bayin Allah waɗanda aka tsarkake.”

170. (Yayin da Alƙur’ani ya zo musu) sai suka kafirce da shi; to ba da daɗewa ba za su sani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai cewa, lalle su da abin da suke bauta wa ba Allah ba, ba su da ikon ɓatar da wani daga kan hanyar gaskiya sai wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zartar masa da hukuncin cewa shi ɗan wuta ne. To wannan shi ne wanda hukuncin Allah zai tabbata a kansa, sai ko ya kafirta ya mutu ya shiga wutar Jahannama. Don haka kada mushirikai su zaci cewa suna da wani iko su da allolinsu na ƙarya a kan ɓatar da muminai daga hanyar Allah su koma ga kafirci. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mala’iku sun tabbatar da matsayinsu na kasancewarsu bayin Allah masu yi masa cikakkiyar biyayya, ba sa saɓa masa daidai da ƙiftawar ido, domin kowanne a cikinsu yana da wani matsayi sananne na bautar Allah da yi masa ɗa’a, kuma dukkansu masu tsayuwa ne sahu-sahu suna bautar sa, hakanan suna tasbihi da tsarkake shi daga duk wata siffa wadda ba

ta kamace shi ba, don haka su sun nesanta kansu daga duk ƙarairayin da mushirikai suke yi game da su da kiran su ‘ya’yan Allah mata.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin cika-baki da mushirikan Makka suka riƙa yi kafin a aiko musu da Manzon Allah (ﷺ) inda suke riya cewa, da a ce suna da wani littafi irin na mutanen farko, watau kamar Attaura da Allah ya saukar wa Banu Isra’ila, to da su ma sun kasance bayin Allah masu tsarkake ibada gare shi don su zama zaɓaɓɓu a wurinsa, alhalin kuwa ƙarya suke yi, domin ga shi nan Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da Alƙur’ani amma sun ƙaryata shi sun kafirce wa abin da ya zo musu da shi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya razana su da cewa ba da daɗewa ba za su gamu da abin da yake jiran su na azaba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sunnar Allah ta gudana a kan ba wa manzanninsa galaba da ƙarfin hujja.

2. Albishir ga muminai waɗanda suka siffantu da zamantowarsu rundunar Allah da cewa, Allah zai ba su nasara ya ɗora su a kan abokan gabarsu.

3. Tsoratar da kafirai masu ƙaryata Manzon Allah daga azabarsa da take dakon su ba da daɗewa ba.

4. Wautar kafirai masu gaggauto wa da kawunansu azabar Allah maimakon su roƙi shiriya daga gare shi.

5. Lokacin da azabar Allah ta zo wa kafirai, imaninsu ba zai amfana musu komai ba.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkaka daga duk wata sifa ta nakasa da tawaya, ya kuma siffanta da duk wata siffa ta kamala da ɗaukaka.

7. Manzannin Allah sun kuɓuta daga kowace irin cuta ta kafirci da munafurci da riya da hassada da duk wata cuta ta zuciya; maganganunsu kuma sun kuɓuta daga ƙarya da yaudara, duk kuwa abin da suka danganta wa Allah Ubangijinsu gaskiya ne.

Suratus Saffat (171-182)
وَلَقَدۡ سَبَقَتۡ كَلِمَتُنَا لِعِبَادِنَا ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٧١ إِنَّهُمۡ لَهُمُ ٱلۡمَنصُورُونَ ١٧٢ وَإِنَّ جُندَنَا لَهُمُ ٱلۡغَٰلِبُونَ ١٧٣ فَتَوَلَّ عَنۡهُمۡ حَتَّىٰ حِينٖ ١٧٤ وَأَبۡصِرۡهُمۡ فَسَوۡفَ يُبۡصِرُونَ ١٧٥ أَفَبِعَذَابِنَا يَسۡتَعۡجِلُونَ ١٧٦ فَإِذَا نَزَلَ بِسَاحَتِهِمۡ فَسَآءَ صَبَاحُ ٱلۡمُنذَرِينَ ١٧٧ وَتَوَلَّ عَنۡهُمۡ حَتَّىٰ حِينٖ ١٧٨ وَأَبۡصِرۡ فَسَوۡفَ يُبۡصِرُونَ ١٧٩ سُبۡحَٰنَ رَبِّكَ رَبِّ ٱلۡعِزَّةِ عَمَّا يَصِفُونَ ١٨٠ وَسَلَٰمٌ عَلَى ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٨١ وَٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٨٢

171. Haƙiƙa kuma kalmarmu (ta ba da nasara) ta rigaya ga bayinmu manzanni.

172. Lalle su tabbas su ne ababen taimako.

173. Kuma lalle rudunarmu tabbas su ne masu yin galaba.

174. Sai ka rabu da su har zuwa wani lokaci.

175. Kuma ka ganar da su (sakamakon kafirci), sannan ba da daɗewa ba za su gani.

176. Yanzu azabarmu suke neman gaggautowa?

177. To lokacin da (azabar) ta sauka a sararin gidajensu, ai asubar waɗanda aka yi wa gargaɗi ta munana.

178. Kuma ka rabu da su har zuwa wani lokaci.

179. Ka kuma ganar (da su sakamakon kafirci), ba da daɗewa ba za su gani.

180. Ubangijinka wanda yake Ubangiji ne Mabuwayi Ya tsarkaka daga abin da suke sifanta (Shi da shi).

181. Aminci kuma ya tabbata bisa ga manzanni.

182. Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

A ayoyin ƙarshe na wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa ya riga ya yi alƙawari tun farko ga manzanninsa da cewa, su ne za su yi nasara a kan abokan gabarsu bisa ga hujja da Allah ya hore musu, ya kuma tabbatar musu da cewa lalle rundunarsa waɗanda suke yaƙi domin ɗaukaka addininsa su ne za su yi galaba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya kawar da kansa daga mushirikai masu nuna masa tsangwama da ƙiyayya, har zuwa wani lokaci sananne a wurin Allah, yayin da azabarsa za ta afka musu, don haka ya saurara musu ya ga abin da zai same su na azabar Allah, su ma ba da daɗewa ba za su gane lokacin da ganewar ba za ta amfane su ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da su game da gaggauto da azabarsa da suke yi da cewa, lokacin da azabarsa za ta sauka gare su, to asubahinsu ta wannan ranar ta muninta ya tsananta.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya yi wa Yahudawan Khaibara sammako a lokacin da su kuma sun fita zuwa gonakinsu da fartanyoyinsu. Lokacin da suka yi kiciɓis da Manzon Allah (ﷺ) sai suka juya a guje suna cewa ga Muhammadu nan da rundunarsa. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allahu Akbar, Khaibara ta rushe! Lalle mu duk mutanen da muka dira a farfajiyar gidajensu, to asubar waɗanda aka yi wa gargaɗi ta munana.” [Bukhari #371 da Muslim #1365].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya kawar da kansa daga waɗannan mushirikai ya ƙyale su har zuwa lokacin da Allah zai yanke hukuncinsa a kansu, ya saurara ya jira lokacin zuwan azabarsa a gare su, su ma za su gani.
A ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rufe Surar da tsarkake kansa daga dukkan tawaya da aibu da mushirikai suke danganta shi da su. Ya tabbatar da aminci da yabo ga manzanninsa, kuma dukkan yabo da kirari da godiya sun tabbata gare shi; shi ne Ubangijin halittu baki ɗaya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman matsayin Alƙur’ani. Don haka wajibi ne muminai su yi imani da shi, su rungume shi da hannu bibbiyu domin karanta shi da fito da ma’anoninsa, sannan su yi aiki da su.

2. Alƙur’ani littafi ne da ya ƙunshi tunatarwa ga mutane game da abin da zai amfane su a rayuwarsu ta duniya da ta lahira, domin ya ƙunshi ilimin sanin Allah da siffofinsa da sunayensa da ayyukansa, da kuma ilimin hukunce-hukuncen shari’a da bayani a kan ranar lahira da sakamakon ayyuka masu kyau da munana.

3. Karatun Alƙur’ani shi ne zikiri mafi ɗaukakar kowane irin zikiri.

4. Ƙafirai ba za su taɓa daina kafircinsu da saɓa wa Allah da Manzonsa ba. Za su ci gaba da taurin kansu da shisshiginsu.

5. Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da tunantar da shi cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka mutanen da suka ƙaryata manzanninsa, don haka su ma waɗannan mushirikan masu ƙaryata shi ba su fi ƙarfin ya hallaka su ba idan sun ƙi tuba su bi shi.

6. Gargaɗin masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da cewa ba za su gagare shi ba idan ya so hallaka su kamar yadda ya hallaka waɗanda suka gabace su.

7. Maƙiya manzannin Allah da muminai sun riƙa jifan su da miyagun sunaye, don su haddasa ƙiyayyarsu a zukatan mutane, ko su tilasta wa manzannin da mabiyansu su daina faɗar gaskiya da yaɗa ta a bainar jama'a.

8. Mushirikan farko sun fahimci ma'anar '*La Ilaha illallahu*' wadda Manzon Allah (ﷺ) yake kiran su zuwa gare ta cewa, tana nufin su yi watsi da duk wani abin bauta ba Allah ba, su tsantsanta bautarsu ga Allah shi kaɗai. Wannan ya sanya suka riƙa mamakin Manzon Allah (ﷺ) da yake so sai sun faɗi wannan kalma, don haka suka bijire masa suka ƙi faɗar ta.

9. Wajabcin fara da'awa da kira zuwa ga Tauhidi kafin sauran hukunce-hukuncen addini.

10. Tsoron da mushirikai suka riƙa ji na tasirin da da'awar Manzon Allah (ﷺ) za ta yi a cikin jama'arsu, don haka ne suka riƙa yi wa junansu wasiyya game da tsayuwa da haƙuri a kan bautar allolinsu, da guje wa duk wani wuri inda ake kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai.

11. Tunanin matsayi na duniya shi ne ya mamaye ƙwaƙwalen mushirikai da har suke ganin bai dace Allah ya ba wa Annabi Muhammadu (ﷺ) manzanci ba, alhali ga manyan Kuraishawa bai saukar musu da komai ba.

12. Taskokin Allah ba a hannun kowa suke ba, suna a hannunsa ne shi kaɗai, don haka babu wanda ya isa ya hana abin da ya ba wa bawansa, ko ya ba wa wani wanda Allah ya hana.

13. Tsananin ƙarfin Allah. Duk yawan rundunar kafirci da ƙarfinta ba komai ba ce a wurin Allah, shi mai iya karya ta ne duk sanda ya ga dama.

38-Suratu Sad

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan da ta shahara da shi shi ne '*Suratu Sad*', watau harafin farko da aka buɗe ta da shi.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa ita Sura ce *Makkiyya*, watau ta sauka gabanin hijira zuwa Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta talatin da takwas (38) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan Suratul Kamar *gabanin Suratul A'araf.*

4. Adadin ayoyinta:
Adadin ayoyinta a lissafin mutanen Kufa tamanin da takwas ne (88). A wurin mutanen Hijaz da Sham da Basra kuma adadinsu tamanin da shida ne (86).

5. Babban Jigonta:
Wannan Sura ta tattauna batutuwa ne da suka danganci Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta da batun manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ) da batun ranar lahira, tare da bayanin mummunar makomar masu faɗa da gaskiya.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tsawatarwa ga mushirikai game da ƙaryata Annabi (ﷺ) da tsoratar da su da irin abin da ya auka wa al'ummun da suka gabace su na azaba, kada su ma ya same su.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da nuna masa ya yi haƙuri kamar yadda annabawan da suka gabace shi suka yi haƙuri, kamar Annabi Ayyuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kuma yabo ga Annabi Dawud da Annabi Sulaiman.
• Tabbatar da tashi bayan mutuwa domin yi wa mutane sakayya a kan ayyukansu masu kyau da munana.
• Bayanin wasu abubuwa da za su faru a ranar alƙiyama.
• Kissar Annabi Adamu da Iblis.

Suratu Sad (1-11)

صٓۚ وَٱلۡقُرۡءَانِ ذِي ٱلذِّكۡرِ ۝١ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي عِزَّةٖ وَشِقَاقٖ ۝٢ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا مِن قَبۡلِهِم مِّن قَرۡنٖ فَنَادَواْ وَّلَاتَ حِينَ مَنَاصٖ ۝٣ وَعَجِبُوٓاْ
أَن جَآءَهُم مُّنذِرٞ مِّنۡهُمۡۖ وَقَالَ ٱلۡكَٰفِرُونَ هَٰذَا سَٰحِرٞ كَذَّابٌ ۝٤ أَجَعَلَ ٱلۡأٓلِهَةَ إِلَٰهٗا وَٰحِدًاۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَيۡءٌ عُجَابٞ ۝٥ وَٱنطَلَقَ ٱلۡمَلَأُ مِنۡهُمۡ أَنِ
ٱمۡشُواْ وَٱصۡبِرُواْ عَلَىٰٓ ءَالِهَتِكُمۡۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَيۡءٞ يُرَادُ ۝٦ مَا سَمِعۡنَا بِهَٰذَا فِي ٱلۡمِلَّةِ ٱلۡأٓخِرَةِ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا ٱخۡتِلَاقٌ ۝٧ أَءُنزِلَ عَلَيۡهِ ٱلذِّكۡرُ مِنۢ بَيۡنِنَاۖ
بَلۡ هُمۡ فِي شَكّٖ مِّن ذِكۡرِيۖ بَل لَّمَّا يَذُوقُواْ عَذَابِ ۝٨ أَمۡ عِندَهُمۡ خَزَآئِنُ رَحۡمَةِ رَبِّكَ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡوَهَّابِ ۝٩ أَمۡ لَهُم مُّلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا
بَيۡنَهُمَاۖ فَلۡيَرۡتَقُواْ فِي ٱلۡأَسۡبَٰبِ ۝١٠ جُندٞ مَّا هُنَالِكَ مَهۡزُومٞ مِّنَ ٱلۡأَحۡزَابِ ۝١١

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. SAD. “Na rantse da Alƙur’ani ma’abocin ɗaukaka.

2. Sai dai waɗanda suka kafirta suna cikin girman kai ne da jayayya.

3. Al'ummu nawa Muka hallaka gabaninsu, sai suka yi ta kururuwar neman agaji, alhali kuwa lokacin ba na neman tsira ba ne.

4. Suka kuma yi mamaki don mai gargaɗi ya zo musu daga cikinsu; kuma kafirai suka ce: “Wannan mai sihiri ne babban maƙaryaci.

5. “Yanzu yaya zai mayar da alloli Allah guda ɗaya? Lalle wannan abu ne mai ban mamaki.”

6. Manyansu kuma suka tafi (suna cewa): “Ku yi tafiyarku, kuma ku yi haƙuri a kan (bautar) allolinku; lalle wannan wani shiryayyen abu ne ake nufi.

7. “Ba mu taɓa jin irin wannan ba a addinin da ya wuce, wannan ba komai ba ne sai ƙage.

8. “Yanzu a saukar masa da Alƙur'ani a tsakaninmu?” Ba haka ba ne, su dai suna ƙokwanto ne game da tunatarwata; bar su, ai har yanzu ba su ɗanɗani azabata ba ne.

9. Ko kuwa a wurinsu ne taskokin rahamar Ubangijinka Mabuwayi Mai baiwa suke?

10. Ko kuma mulkin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu nasu ne? To sai su kama hanyoyin zuwa sama (domin su aikata abin da suke so).

11. (Waɗannan) wata runduna ce da za a murƙushe ta, kamar sauran al’ummun da suka gabata (waɗanda suka ƙaryata manzanninsu).

An buɗe wannan sura da hafarin ‘Sad’, kamar yadda aka buɗe wasu surori da haruffa irinsa. [Dubi tafsirinmu na farkon *Suratul Baƙara* domin ƙarin bayani a kan waɗannan haruffan].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da Alƙur’ani ma’abocin ɗaukaka wanda kuma ya ƙunshi tunatar da mutane da abin da zai amfane su a duniya da lahira. Ya kuma bayyana cewa kafirai maimakon su yi imani da Alƙur’ani sai suka yi girman kai game da Tauhidi, suka kuma dinga saɓani da Annabi (ﷺ) da nuna masa ƙiyayya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da su da cewa ya hallaka al’ummu da dama a gabaninsu yayin da suka ƙaryata manzanninsa. Kuma lokacin da azabar Allah ta zo musu sun yi ta kururuwar neman taimako domin a tserar da su, to amma sun makaro, domin lokacin tsira ya riga ya wuce, don haka suka yi ta ihu a banza. Saboda haka su ma kafiran wannan al’umma lallai su shiga taitayinsu kafin irin haka ya faru gare su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai sun riƙa mamakin wai ta yaya wani manzo zai zo daga cikinsu yana yi musu gargaɗi game da azabar Allah idan ba su bar abin da suke yi na kafirci ba. Maimakon su saurare shi su gaskata shi sai suka shiga tuhumar sa da cewa, shi mai sihiri ne da yake sihirce mutane suna bin shi, kuma maƙaryaci ne yana da’awar manzanci ne kawai ba bisa gaskiya ba. Suka kuma ƙaryata duk wasu hujjoji da ya nuna musu na manzancinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa babban abin da ya ba wa kafirai mamaki game da Annabi (ﷺ) shi ne wai ta yaya zai mayar da ababen bauta su zama ɗaya, watau shi ne Allah? Suna ganin wannan abu ya isa abin mamaki a gare su.

Daga nan sai manyansu suka tafi suna faɗa wa mabiyansu cewa su ci gaba da tabbata a kan abin da suke kai na bautar gumakansu, kada su sake su, kada wanda ya kuskura ya shiga addinin Muhammadu (ﷺ), su ƙanƙame wa addinin iyaye da kakanni. Suka kuma nuna wa mabiyansu cewa wai abin da Annabi (ﷺ) yake kiran su zuwa gare shi na bautar Allah shi kaɗai wani shiryayyen abu ne da ya ƙulla don ya mallake su su zama mabiyansa. Kuma wannan addini da ya zo musu da shi sabo ne a wurinsu, wai su ba su taɓa jin labarin bautar Allah shi kaɗai ba daga wurin iyayensu, ko ma a cikin addinin Annabi Isa, ba su taɓa jin an ce a kaɗaita abin bauta ba; su wannan abu da ake faɗa musu ba komai ba ne sai tantagaryar ƙarya.
Kuma wani babban abin takaici da ban haushi a wurinsu shi ne wai a rasa wanda za a ba wa manzanci a saukar masa da wahayi a tsakaninsu sai Annabi Muhammadu (ﷺ), alhali su ne manyan mutane da suka fi cancanta, amma ba a saukar musu da komai ba? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa ba haka ne ba, su dai kawai suna kokwanto ne game da wahayin da ya yi wa Manzonsa, kuma har yanzu ba su ɗanɗani azabarsa ba ne; sun kuma ruɗu da saurara musu da ya yi. Da a ce sun ɗanɗani azabar Allah da ba su riƙa zaƙewa cikin kafirci da kokwanton wahayi ba.
Game da jayayyar da suke yi kuma a kan an bai wa Annabi Muhammadu (ﷺ) manzanci ba a ba wa wani daga cikin manyansu ba, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su cewa, shin ko taskokin rahamarsa mallakarsu ne, don haka su ne za su zaɓi wanda zai yi wa baiwa da manzanci da wanda zai hana? Babu shakka taskokin komai a hannun Allah suke, shi ne yake zaɓar wanda ya ga dama ya ba shi annabta.
Sannan ya sake tambayar su cewa, shin ko su ne suke da mulkin sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu, don haka suka zamanto su ne masu haƙƙin bayarwa ko hanawa? Idan har sun ce haka ne to ai sai su kama hanyar da za ta kai su zuwa saman don su riƙa zartar da hukuncin bayarwar da hanawar daga can. Su ma kuwa sun san ba haka abin yake ba. Mulkin sammai da ƙasa da duk abin da suka ƙunsa a hannun Allah suke shi kaɗai, yana kuma aikata abin da ya ga dama babu mai ikon hana shi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, su waɗannan kafiran masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) wata `yar ƙaramar runduna ce da za a murƙushe ta cikin sauƙi kamar yadda aka murƙushe rundunonin da suka gabace ta yayin da suka ƙaryata manzannin da Allah ya aiko musu. Don haka duk yadda suka haɗa ƙarfi don su karya tsarin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi ba za su yi nasara ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafiran al'ummun da suka gabaci wannan al'umma sun fi haɗuwa da yin gangami a kan kafirci da faɗa da gaskiya, amma duk da haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su baki ɗaya. Don haka waɗannan kafiran masu ƙaryata Manzonsa (ﷺ) ba su isa komai ba, idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya so hallaka su to yin hakan ya fi komai sauƙi a wurinsa.

2. Duk wanda ya ƙaryata manzo ɗaya, to kamar ya ƙaryata dukkan manzannin Allah ne, domin saƙo iri ɗaya suka zo da shi na batun Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta.

3. Karyata manzannin Allah shi ne yake sanadiyyar saukar azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Tsananin taurin kan mushirikai; a maimakon su roƙi Allah shiriyarsa sai suke roƙon sa ya gaggauto musu da azabarsa tun a duniya. Wannan yana nuna tsananin wauta da rashin hankali irin na kafirai.

Suratu Sad (12-16)
كَذَّبَتۡ قَبۡلَهُمۡ قَوۡمُ نُوحٖ وَعَادٞ وَفِرۡعَوۡنُ ذُو ٱلۡأَوۡتَادِ ١٢ وَثَمُودُ وَقَوۡمُ لُوطٖ وَأَصۡحَٰبُ لۡـَٔيۡكَةِۚ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلۡأَحۡزَابُ ١٣ إِن كُلٌّ إِلَّا كَذَّبَ ٱلرُّسُلَ فَحَقَّ عِقَابِ ١٤ وَمَا يَنظُرُ هَٰٓؤُلَآءِ إِلَّا صَيۡحَةٗ وَٰحِدَةٗ مَّا لَهَا مِن فَوَاقٖ ١٥ وَقَالُواْ رَبَّنَا عَجِّل لَّنَا قِطَّنَا قَبۡلَ يَوۡمِ ٱلۡحِسَابِ ١٦

12. Mutanen Nuhu sun ƙaryata kafin su (mutan Makka) da Adawa da Fir’auna mai turaku.

13. Da kuma Samudawa da mutanen Luɗu da mutanen Sarƙaƙiya. Waɗannan su ne al’ummun.

14. Babu ɗaya daga cikinsu wanda bai ƙaryata manzanni ba, sai uƙubata ta wajaba (a kansu).

15. Kuma ba abin da waɗannan suke sauraro sai busa guda ɗaya wadda ba ta da makawa.

16. Suka kuma ce: “Ya Ubangijinmu, Ka gaggauto mana rabonmu (na azaba) tun kafin ranar hisabi!”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci al’ummu shida da suka gabata waɗanda suka ƙaryata manzannin da ya aika musu ya kuma hallaka su baki ɗaya don wannan ya zamanto darasi da izina ga mushirikai masu faɗa da gaskiyar da Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da ita.
Na farko, su ne al’ummar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka ƙaryata shi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ya hallaka su da ruwan Ɗufana.
Na biyu, su ne Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su ma sun ƙaryata Annabinsu Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ya hallaka su da iska mai ƙaraji da ƙarfi.
Na uku, su ne Fir’auna da mutanensa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta Fir'auna da mai turaku waɗanda a jikinsu ne yake ɗaure Banu Isra’ila yana gana musu azaba. Da shi da rundunarsa duka Allah ya nutsar da su a cikin ruwa.
Na huɗu, Samudawa mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sun ƙaryata shi, su ma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su da tsawa.
Na biyar, su ne mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sun ƙaryata Annabinsu Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kifar da garinsu, ya kuma bi su da ruwan duwatsu na wuta.
Na shida, su ne mutanen Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda su ma sun ƙaryata Manzonsu Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai Allah ya hallaka su gaba ɗayansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗannan al’ummu su ne rundunonin da suka haɗu a kan ƙaryata manzannin Allah da kafirce wa saƙon da suka zo da shi na gaskiya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa babu ɗaya daga cikin waɗannan al’ummu da bai ƙaryata manzanninsa ba, don haka uƙubarsa ta cancanta gare su, ya saukar musu da azabarsa yayin da lokacin zuwanta ya yi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kafiran da suke ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) babu abin da suke sauraro sai zuwan lokacin da za a yi busar ƙaho ta biyu wadda babu tababa game da faruwarta, dole sai ta auku. Idan ta zo to a lokacin azabar Allah za ta tabbata a kansu matuƙar sun mutu ba su tuba ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin izgili da gatsali da kafirai suke yi wa Allah game da tsoratar da su azabarsa da yake yi, suna kira suna roƙon sa cewa ya gaggauto musu da kasonsu na azaba tun a nan duniya ba sai an jira alƙiyama ta tsaya ba ranar da za a yi musu hisabi. Watau suna nuna cewa Manzon Allah (ﷺ) yana faɗa musu ƙarya ne game da batun azabar lahira, idan kuwa gaskiya ne to su fara gani tun daga nan duniya ba sai an je lahira ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin Annabi (ﷺ) da umartar sa da yin haƙuri a kan muzgunawar mushirikai da miyagun maganganunsu a gare shi.

2. Kyakkyawan yabo ga Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

3. Falalar yawan tuba da mayar da dukkan al'amari ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Ɗimbin falala da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

5. Tabbatar da cewa daskararrun abubuwa kamar duwatsu da kuma sauran halittu kamar tsuntsaye su ma suna yin tasbihi da tsarkake Allah, sai dai kawai mu ne ba ma jin abin da suke faɗa.

Suratu Sad (17-20)
ٱصۡبِرۡ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَٱذۡكُرۡ عَبۡدَنَا دَاوُۥدَ ذَا ٱلۡأَيۡدِۖ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٞ ١٧ إِنَّا سَخَّرۡنَا ٱلۡجِبَالَ مَعَهُۥ يُسَبِّحۡنَ بِٱلۡعَشِيِّ وَٱلۡإِشۡرَاقِ ١٨ وَٱلطَّيۡرَ مَحۡشُورَةٗۖ كُلّٞ لَّهُۥٓ أَوَّابٞ ١٩ وَشَدَدۡنَا مُلۡكَهُۥ وَءَاتَيۡنَٰهُ ٱلۡحِكۡمَةَ وَفَصۡلَ ٱلۡخِطَابِ ٢٠

17. (Sai Allah Ya ce): "Ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, ka kuma tuna bawanmu Dawuda ma'abocin ƙarfi; lalle shi ya kasance mai yawan komawa ne (ga Allah).

18. Lalle Mu Mun hore masa duwatsu suna yin tasbihi tare da shi a yamma da hantsi

19. Da kuma tsuntsaye a tattare; dukkaninsu suna biyayya a gare shi.

20. Kuma Muka ƙarfafa mulkinsa, Muka kuma ba shi hikima da bayyana hukunce-hukunce (tsakanin masu husuma).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya yi haƙuri game da maganganu marasa daɗi da kafirai suke faɗa masa da izgilin da suke yi wa maganar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ya umarce shi da ya tuna bayin Allah manzannin da suka gabace shi da haƙurin da suka yi wajen bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Bayin nasa kuwa su ne, Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda Allah ya ba shi ƙarfin karo da maƙiyansa da ƙarfin juriya wajen bautar Allah. Allah ya yabe shi da cewa shi mutum ne mai yawan tuba yana komawa zuwa ga Allah yana aikin da zai jawo masa yardarsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Sallar da Allah ya fi so ita ce sallar (Annabi) Dawud; azumin da Allah ya fi so shi ne azumin (Annabi) Dawud; ya kasance yana barci rabin dare, ya yi tsayuwar salla gwargwadon sulusinsa (watau ɗaya bisa ukun dare); ya yi kuma barci na sudusinsa (watau kaso ɗaya bisa shida na dare); yana kuma azumi rana ɗaya ya sha rana ɗaya (watau yana tsallaken kwana ɗaya-ɗaya)." [Bukhari #1131 da Muslim #1159].

A wata ruwaya Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kuma ba ya ja da baya a lokacin karo da abokan gaba." [Bukhari #1977 da Muslim #1159].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu manya-manyan ni'imomi da ya yi wa Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi):

Ta ɗaya, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya hore masa duwatsu suna tasbihi tare da shi da yamma da kuma hantsi.

An karɓo daga Ummu Hani ‘yar Abu Ɗalib Allah ya yarda da ita, ta ce: “Annabi (ﷺ) ya shigo wurina a ranar *Fathu Makka* ƙura ta lulluɓe shi, sai ya nemi a kawo masa kwatanniya, sai na ga alamar ɓirɓishin tuƙaƙƙen gari a cikinta, sai na zuba masa ruwa a cikinta sai ya yi umarni a sanya labule tsakanina da shi. Sai ya shiga ya yi wanka da wannan ruwan, sannan sai ya tashi ya yi sallar walaha raka’a takwas.” Mujahid ya ce: “Na faɗa wa Abdullahi ɗan Abbas wannan hadisin sai ya ce: ‘Wannan ita ce sallar safiya.’” [Ɗabarani, *Al-Mu’ujamul Kabi*r #1070].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Babu mai kiyaye sallar walaha sai mai yawan komawa ga Allah.” Ya ce: “Ita ce sallar masu yawan komawa ga Allah.” [Ibn Khuzaima #1224].

Ta biyu, ya bayyana cewa, ya hore masa tsuntsaye suna taruwa a gabansa, dukkansu kuma suna biyayya a gare shi, suna yin tasbihi tare da shi.
Ta uku, Allah ya ƙarfafa masa mulkinsa ya kuma ba shi kwarjini sannan kuma ga ƙarfin jiki, da kuma nasarar da ya ba shi a kan maƙiyansa.
Ta huɗu, ya ba shi annabta, wadda ta ƙunshi cikakken ilimi da kyakkyawan aiki.**Ta biyar**, ya ba shi zalaƙa ya kuma hore masa iya bayani dalla-dalla da sasanta masu husuma.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haura wa gidajen mutane ta katanga ba da saninsu ba jefa tsoro ne a cikin zukatansu, bai halatta ba a shari’a.

2. Annabawa sukan ji tsoron abin tsoro, kamar sauran mutane.

3. Wajibi ne a kan duk wanda ya tsoratar da wani, to ya kwantar masa da hankali da maganar da za ta sanya shi ya samu nutsuwa.

4. Waɗannan mutane biyu da suka hauro wa Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wurin ibadarsa sun nuna rashin ladabi ta fuska biyu:
Fuska ta farko, yayin da suka hauro ta kan katanga.
Na biyu, yayin da suke umartar sa da cewa, ya yi musu hukunci da gaskiya, domin wannan zai iya haifar da tuhumar cewa ba ya hukunci da gaskiya, alhali kuwa shi annabi ne da bai halatta a yi masa irin wannan mummunan zato ba.

5. Rashin godiyar wasu mutane da Allah ya ba su tarin dukiya amma koyaushe tunanin yadda za su mallake ta wasu suke.

6. Halaccin mutum biyu ko fiye da haka su haɗa dukiyarsu wuri guda domin yin sana’a tare ko wani aiki.

7. Duk sanda imanin mutum ya yi ƙarfi ya yawaita ayyuka nagari, yakan nisanci zaluntar mutane ko cutar da su.

8. Masu imani da ayyuka na ƙwarai ‘yan kaɗan ne a cikin mutane.

9. Yawancin masu haɗa dukiyarsu domin gudanar da sana’a, sukan zalunci junansu.

10. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan iya jarrabar annabawansa, don ƙara musu martaba da matsayi a wurinsa.

11. Istigfari yana kankare zunubai.

12. Faɗuwa a yi sujjada ga Allah domin ƙasƙantar da kai a gabansa sunna ce ta annabawa.

13. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yafe wa duk wanda ya yi laifi ya nemi yafiyarsa.

Suratu Sad (21-25)

*وَهَلۡ أَتَىٰكَ نَبَؤُاْ ٱلۡخَصۡمِ إِذۡ تَسَوَّرُواْ ٱلۡمِحۡرَابَ ٢١ إِذۡ دَخَلُواْ عَلَىٰ دَاوُۥدَ فَفَزِعَ مِنۡهُمۡۖ قَالُواْ لَا تَخَفۡۖ خَصۡمَانِ بَغَىٰ بَعۡضُنَا عَلَىٰ بَعۡضٖ فَٱحۡكُم بَيۡنَنَا بِٱلۡحَقِّ وَلَا تُشۡطِطۡ وَٱهۡدِنَآ إِلَىٰ سَوَآءِ ٱلصِّرَٰطِ ٢٢ إِنَّ هَٰذَآ أَخِي لَهُۥ تِسۡعٞ وَتِسۡعُونَ نَعۡجَةٗ وَلِيَ نَعۡجَةٞ وَٰحِدَةٞ فَقَالَ أَكۡفِلۡنِيهَا وَعَزَّنِي فِي ٱلۡخِطَابِ ٢٣ قَالَ لَقَدۡ ظَلَمَكَ بِسُؤَالِ نَعۡجَتِكَ إِلَىٰ نِعَاجِهِۦۖ وَإِنَّ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلۡخُلَطَآءِ لَيَبۡغِي بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٍ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَقَلِيلٞ مَّا هُمۡۗ وَظَنَّ دَاوُۥدُ أَنَّمَا فَتَنَّٰهُ فَٱسۡتَغۡفَرَ رَبَّهُۥ وَخَرَّ رَاكِعٗا وَأَنَابَ۩ ٢٤ فَغَفَرۡنَا لَهُۥ ذَٰلِكَۖ وَإِنَّ لَهُۥ عِندَنَا لَزُلۡفَىٰ وَحُسۡنَ مَـَٔابٖ ٢٥

21. Shin labarin abokan husuma ya zo maka, yayin da suka haura wurin ibada?

22. Yayin da suka shiga wurin Dawuda sai ya tsorata da su, suka ce: “Kada ka tsorata, (mu biyun nan) masu husuma ne, ɗayanmu ya zalunci ɗaya, sai ka yi hukunci a tsakaninmu da gaskiya, kada kuma ka yi zalunci, kuma ka shiryar da mu hanya madaidaiciya.

23. “Lalle wannan ɗan’uwana ne yana da awaki guda casa’in da tara, ni kuma ina da akuya guda ɗaya, sai ya ce: ‘Ka ba ni ita;’ ya kuma rinjaye ni game da maganar.”

24. (Dawuda) Ya ce: “Haƙiƙa ya zalunce ka saboda neman haɗe akuyarka cikin awakinsa; kuma lalle yawancin masu haɗa dukiyarsu tabbas wasunsu suna zaluntar wasu, sai fa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, su kuwa kaɗan ne ƙwarai. Sai kuma Dawuda ya tabbata cewa Mun jarraba shi ne, sai ya nemi gafarar Ubangijinsa, ya kuma faɗi yana sujjada kuma ya koma (ga Allah).

25. Sai Muka gafarta masa wannan; lalle kuma yana da kusanci da Mu da kuma kyakkyawar makoma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa (ﷺ) wani labari mai ban al’ajabi da ya faru da Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da wasu mutum biyu masu jayayya da juna suka hauro masa ta katanga a wurin ibadarsa. Lokacin da suka faɗo masa ba zato ba tsammani sai ya tsorata da su, don a zatonsa sun zo su cutar da shi ne, musamman ganin sun shigo masa ta wata hanya da bai saba ganin an shigo masa daga gare ta ba. Da suka fahimci ya tsorata sai suka kwantar masa da hankali suka ce, kada ya tsorata suka bayyana masa cewa su masu jayayya ne a tsakaninsu, ɗayansu ya zalunci ɗaya, don haka suna roƙon sa da ya yi hukunci na adalci a tsakaninsu, ya nuna musu mafita.
Sai ɗayansu ya yi bayanin jayayyar da ta faru a tsakaninsu, da cewa shi da ɗan’uwansa ne wanda yake da awaki casa’in da tara, shi kuma yana da akuya guda ɗaya, to amma sai shi ɗan’uwan nasa ya nemi ya ba shi wannan akuyar tasa guda ɗaya don ya cike ɗari, ya kuma matsa masa da maganar har saura ƙiris ya rinjaye shi da hujja.
Nan take sai Annabi Dawud ya yanke hukunci tsakaninsu, ya shaida wa mai ƙara cewa, lalle ɗan’uwansa ya zalunce shi da ya nemi ya haɗa akuyarsa ɗaya cikin awakinsa. Ya ƙara da cewa wannan da man ita ce al’adar

waɗanda suke haɗa dukiyarsu wuri guda, yawancinsu sukan zalunci abokan tarayyarsu su ƙi yi musu adalci, sai dai mutanen da suka yi imani suka yi ayyuka na ƙwarai su ne suke yin adalci ba sa zaluntar abokan tarayyarsu cikin dukiya; amma kuma waɗannan ‘yan kaɗan ne ƙwarai a cikin mutane.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tabbatar da cewa wannan abu da ya faru da shi na haurowar waɗannan mutane da shigo masa ba zato ba tsammani da kuma ƙarar da suka kawo masa wata jarrabawa ce Allah ya shirya masa, sai ya nemi gafarar Ubangijinsa, ya faɗi ƙasa ya yi sujjada, domin neman kusanci da Allah, ya tuba ya mayar da al’amarinsa ga Allah.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (SAW) ya yi sujjada a *Suratus Sad* (watau daidai aya ta 24) sai ya ce: “Dawud ya yi sujjadar tuba zuwa ga Allah, mu kuma muna yin sujjadar godiya ga Allah.” [Nasa’i #957].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Annabi Dawud da cewa ya gafarta masa, kuma shi Annabi Dawud makusanci ne ga Allah sosai, yana da kuma kyakkyawar makoma a lahira.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shugabancin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Wajibi ne a kan shugaba ko alƙali ya yi wa mutane adalci wajen zartar da hukuncinsa.

3. Girman haɗarin bin son zuciya da kauce wa gaskiya, domin hakan yakan zama sanadiyyar ɓacewa daga hanya madaidaiciya.

4. Duk wanda yake tuna hisabi a ranar lahira, to zai guji aiki da son zuciya.

Suratu Sad (26)
يَٰدَاوُۥدُ إِنَّا جَعَلۡنَٰكَ خَلِيفَةٗ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱحۡكُم بَيۡنَ ٱلنَّاسِ بِٱلۡحَقِّ وَلَا تَتَّبِعِ ٱلۡهَوَىٰ فَيُضِلَّكَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَضِلُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ لَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدُۢ بِمَا نَسُواْ يَوۡمَ ٱلۡحِسَابِ٢٦

26. Ya Dawuda, lalle Mun sanya ka halifa a bayan ƙasa, sai ka yi hukunci a tsakanin mutane da gaskiya, kada ka bi son zuciya sai ya ɓatar da kai daga hanyar Allah. Lalle waɗanda suke ɓacewa daga hanyar Allah suna da (sakamakon) azaba mai tsanani saboda mantawar da suka yi da ranar hisabi.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya kira Annabi Dawud (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sanar da shi cewa ya sanya shi halifa a bayan ƙasa don ya riƙa hukunci tsakanin mutane, ya kuma umarce shi da yi musu hukunci na adalci. Ya kuma yi masa kashedi da cewa kar ya kuskura ya bi son zuciya, ya nuna goyon bayansa ga wani makusanci ko aboki yayin gudanar da shari’a, ko ya ƙi yi wa wani adalci saboda adawar da ke tsakaninsu. Domin bin son zuciya zai ɓatar da shi daga kan hanya madaidaiciya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk wanda ya kauce daga hanyar Allah madaidaiciya to zai haɗu da azaba mai raɗaɗi, saboda ya manta da ranar hisabi, domin tunawa da ita shi zai sa su kauce wa son zuciya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci sammai da ƙasa da duk abin da yake tsakaninsu don wata babbar hikima, watau domin a tsarkake shi da bauta shi kaɗai kada a haɗa shi da komai.

2. Duk wanda yake zaton cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci sammai da ƙasa ba tare da wata hikima ba, to wannan kafiri ne ba mumini ba.

3. Yana daga cikin hikimar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya bambance muminai da kafirai, ko masu tsoron sa da bin umarninsa da masu saɓon sa da keta umarninsa.

4. Imani da Allah da Manzonsa da ayyuka nagari su ne gyaruwar ƙasa. Ƙafirci da saɓon Allah kuwa shi ne ɓarna a bayan ƙasa.

5. Alƙur'ani littafi ne mai cike da albarka, don haka aiki da shi shi yake kai ga samun albarkar rayuwar duniya da ta lahira. Bijire masa kuwa da watsi da karantarwarsa shi yake kai ga taɓarɓarewar rayuwa ta duniya da lahira.

6. Wajabcin karanta Alƙur'ani da tuntuntuni cikin ma'anonin ayoyinsa, domin wannan ita ce babbar manufar saukar da shi.

7. Babu masu wa'azantuwa da karantarwar Alƙur'ani sai mutane masu hankali. Duk wanda Alƙur'ani bai ishe shi wa'azi ba to ba mai lafiyayyen hankali ne ba

Suratu Sad (27-29)

وَمَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَآءَ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا بَٰطِلٗاۚ ذَٰلِكَ ظَنُّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۚ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنَ ٱلنَّارِ ٢٧ أَمۡ نَجۡعَلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ كَٱلۡمُفۡسِدِينَ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَمۡ نَجۡعَلُ ٱلۡمُتَّقِينَ كَٱلۡفُجَّارِ ٢٨ كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ إِلَيۡكَ مُبَٰرَكٞ لِّيَدَّبَّرُوٓاْ ءَايَٰتِهِۦ وَلِيَتَذَكَّرَ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٢٩

27. Kuma ba Mu halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu a banza ba. Wannan zato ne na waɗanda suka kafirta. Saboda haka tsananin azabar wuta ya tabbata ga waɗanda suka kafirce.

28. Shin za Mu mayar da waɗanda suka yi imani suka yi ayyuka nagari kamar masu ɓarna a bayan ƙasa, ko kuma za Mu mayar da masu taƙawa kamar lalatattu?

29. Littafi ne mai albarka da Muka saukar maka da shi domin su yi tuntuntuni game da ayoyinsa, don kuma masu hankula su wa'azantu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimarsa ta halittar sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, da cewa bai halicce su a banza ba, ya tabbatar da cewa wannan zato ne na kafirai wanda bai dace su yi wa Allah shi ba; azabar wutar Jahannama a ranar alƙiyama kuma ta tabbata ga waɗannan kafirai masu irin wannan zato, matuƙar suka mutu ba su tuba ba.
Sai kuma Allah ya bayyana cewa, adalcinsa da hikimarsa sun zartar da cewa ba zai taɓa daidaita mutanen kirki da na banza ba; ba zai kuma daidaita waɗanda suka aikata alheri da waɗanda suka aikata sharri ba, kamar yadda kafirai suke tsammanin babu wani bambanci na sakamako a tsakaninsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su da cewa, yanzu suna ganin zai mayar da waɗanda suka yi imani da shi suka bi Manzonsa suka kuma yi ayyuka nagari su zama daidai da maɓarnata a bayan ƙasa suna yaɗa kafirci da

saɓon Allah? Ko kuma zai daidaita masu kiyaye dokokin Allah suna guje wa haninsa da kafirai ko munafukai waɗanda suka yi dumu-dumu cikin saɓon Allah? Lalle duk mai hankali ya san cewa daidaita tsakanin waɗannan kashe-kashen mutane tsantsar zalunci ne wanda bai dace a jingina wa Allah shi ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin zai saka wa muminai masu tsoron sa da gidan Aljanna, ya kuma saka wa kafirai da gidan wutar Jahannama, domin ba ɗaya suke a wurinsa ba, don haka sakamakonsu ma ba zai zama ɗaya ba.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wannan Alƙur'ani littafi ne mai albarka da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) wanda yake cike da alheri da amfani mai yawa, domin mutane su riƙa tuntuntuni game da ayoyinsa su kuma fahimci ma'anoninsa; masu lafiyayyun hankula kuma su wa'azantu da shi.

1. Yabon da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi ga Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. 'Ya'ya kyauta ce daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bawansa, don haka ya wajaba a yi masa godiya a kansu.

3. Yabon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bawansa da ambaton sa da siffar 'bawan Allah', ba ƙaramin matsayi ba ne.

4. Falalar komawa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da yawan tuba a gare shi.

5. Dukiya ta halal alheri ce ga bawa.

6. Babu laifi ga mumini ya nuna sonsa ga dukiya ta halal, matuƙar ba ta shagaltar da shi daga ambaton Allah ba.

7. Ba ya halatta ga mutum ya shagalta da wani abu na duniya har ya mantar da shi ambaton Allah ko salla a kan lokacinta.

8. Tsananin son Annabi Sulaiman (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ga Ubangijinsa, ya sa ya fifita rabuwa da abin da yake so na dukiya, domin neman yardar Allah da gafararsa.

Suratu Sad (30-33)
وَوَهَبۡنَا لِدَاوُۥدَ سُلَيۡمَٰنَۚ نِعۡمَ ٱلۡعَبۡدُ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٞ ٣٠ إِذۡ عُرِضَ عَلَيۡهِ بِٱلۡعَشِيِّ ٱلصَّٰفِنَٰتُ ٱلۡجِيَادُ ٣١ فَقَالَ إِنِّيٓ أَحۡبَبۡتُ حُبَّ ٱلۡخَيۡرِ عَن ذِكۡرِ رَبِّي
حَتَّىٰ تَوَارَتۡ بِٱلۡحِجَابِ ٣٢ رُدُّوهَا عَلَيَّۖ فَطَفِقَ مَسۡحَۢا بِٱلسُّوقِ وَٱلۡأَعۡنَاقِ ٣٣

30. Muka kuma yi wa Dawuda baiwar (ɗa) Sulaimanu. Madalla da wannan bawan; lalle shi mai yawan komawa ne (ga Allah).

31. (Ka tuna) lokacin da aka jera masa ingarmun dawakai masu tsayawa da ƙafa uku da yamma.

32. Sai ya ce: "Lalle ni na fifita son dukiya (watau dawakai) a kan ambaton Ubangijina (watau sallar La'asar) har sai da (rana) ta faɗi."

33. (Ya ce): "Ku dawo min da su;" sai ya riƙa saran su ta ƙafafu da wuyoyi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya yi wa Annabi Dawuda (Amincin Allah

ya tabbata a gare shi) baiwa da ɗa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) domin ya faranta masa rai ya kuma gaji annabta da ilimi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da yawan komawa ga Allah da tuba a gare shi.
Sai kuma ya tunatar da Manzonsa (ﷺ) da wata baiwa ta tsoron Allah da son bautarsa da ya yi wa bawansa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), lokacin da aka jera masa ingarmun dawakai `yan asali, masu kuma tsayuwa da ƙafa uku su ɗage ta huɗu, a daidai lokacin sallar La'asar, ya riƙa zagaya su suna ba shi sha'awa ainun, bai ankara ba har rana ta faɗi. Da Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya lura da sakacin da ya yi har rana ta faɗi bai yi sallar La'asar ba, sai nadama ta lulluɓe shi ya gane lalle ya fifita son dawakan nan har sun ɗauke masa hankali ya bar zikirin Ubangijinsa, har rana ta faɗi bai ba da faralin La'asar ba, sai ya yi umarni a dawo masa da dawakan gaba ɗayansu. Da aka dawo da su sai ya riƙa bin su ɗaya bayan ɗaya yana sassare ƙafafunsu da wuyoyinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan jarrabi bayinsa nagari da abin da ya ga dama domin ɗaukaka martabarsu.

2. Annabi Sulaiman (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yana da kujerar mulki da yake zama a kanta kamar yadda sarakuna suke yi, domin shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa masa annabta da sarauta a lokaci ɗaya.

3. Al'amarin lahira ya fi muhimmanci a wurin annabawa a kan al'amarin duniya, shi ya sa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fara neman gafarar Allah kafin ya roƙe shi mulkin duniya.

4. Annabawan Allah su ma suna da buƙatar gafarar Allah.

5. Mu'ujizoji masu yawa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

6. Allah mai iko ne a kan komai, don haka ya hore wa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) iska da aljannu da shaiɗanu suka zamo masu bin umarninsa da miƙa wuya a gare shi.

7. Girman mulkin Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda bai taƙaita a kan jinsin ɗan'adam ba; ya kai har ga aljannu da tsuntsaye da iska mai kaɗawa.

8. Ishara game da cewa, kasancewar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shimfiɗa wa bawansa ni'imomin duniya, wannan ba zai sanya ya hana shi ni'imar lahira ba. Abin da ake buƙata ga ɗan'adam shi ne kiyaye dokokin Allah a cikin kowane hali na wadata ko na talauci.

Suratu Sad (34-40)
وَلَقَدْ فَتَنَّا سُلَيْمَٰنَ وَأَلْقَيْنَا عَلَىٰ كُرْسِيِّهِۦ جَسَدًا ثُمَّ أَنَابَ ﴿٣٤﴾ قَالَ رَبِّ ٱغْفِرْ لِى وَهَبْ لِى مُلْكًا لَّا يَنۢبَغِى لِأَحَدٍ مِّنۢ بَعْدِىٓ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْوَهَّابُ ﴿٣٥﴾
فَسَخَّرْنَا لَهُ ٱلرِّيحَ تَجْرِى بِأَمْرِهِۦ رُخَآءً حَيْثُ أَصَابَ ﴿٣٦﴾ وَٱلشَّيَٰطِينَ كُلَّ بَنَّآءٍ وَغَوَّاصٍ ﴿٣٧﴾ وَءَاخَرِينَ مُقَرَّنِينَ فِى ٱلْأَصْفَادِ ﴿٣٨﴾ هَٰذَا عَطَآؤُنَا
فَٱمْنُنْ أَوْ أَمْسِكْ بِغَيْرِ حِسَابٍ ﴿٣٩﴾ وَإِنَّ لَهُۥ عِندَنَا لَزُلْفَىٰ وَحُسْنَ مَـَٔابٍ ﴿٤٠﴾

34. Kuma haƙiƙa Mun jarrabi Sulaimanu Muka ɗora wani jiki a kan gadonsa na mulki, sannan ya koma (kan mulkinsa).

35. Ya ce: “Ya Ubangijina, Ka gafarta min, Ka kuma ba ni wani mulki wanda bai kamaci wani ba a bayana ya sami irinsa; lalle Kai Kai ne Mai yawan kyauta.”

36. Sai Muka hore masa iska tana tafiya da umarninsa a natse duk inda ya fuskanta.

37. Da kuma shaiɗanu masu yin kowane irin gini da kuma masu yin nutso (a ruwa).

38. Wasu kuma an ɗaɗɗaure su cikin maruruwa.

39. Wannan kyautarmu ce, to ka yi kyauta ko ka hana ba da wani bincike ba.

40. Lalle kuma shi tabbas yana da kusanci a wurinmu, da kuma kyakkyawar makoma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata jarrabawa da ya yi wa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) game da mulkinsa, lokacin da ya ɗora wani jiki a kan kujerarsa ta mulki.

An ruwaito maganganu da dama game da wannan jiki da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗora a kan kujerar mulkin Annabi Sulaimanu. Yawancinsu maganganu ne marasa inganci. Mafi ingancin waɗanda aka ambata a nan guda biyu ne:

Na farko, wani shaiɗani ne Allah ya ba shi damar hawa kan kujerar mulkin Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a matsayin shi ne Annabi Sulaimanu, ya yi ta gudanar da mulki na tsawon wasu ‘yan kwanaki, sannan daga baya mulkin ya dawo hannun Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Allah kuma ya hore masa iko da sarrafa shaiɗanu. Wannan shi ne ra’ayin da yawancin malaman tafsiri suka fi amincewa da shi.
Na biyu, ya yi rantsuwa ne a kan zai kewaya ɗakunan matansa su ɗari a dare ɗaya, kuma kowacce za ta ɗauki ciki ta haifi jarumin mayaƙi da zai yi jihadi don ɗaukaka kalmar Allah, sai ya manta bai ce ‘*in sha’ Allahu*’ ba, sai ya zamanto mace ɗaya ce a cikinsu ta sami ciki, ita ma kuma sai ta haifa masa rabin mutum. [Dubi, Bukhari #3424 da Muslim #1654]. To wannan shi ne jikin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata, kamar yadda wasu malamai suke gani. Amma dai magana ta farko ta fi ƙarfi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka)ya bayyana cewa Annabi Sulaimanu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi nadama a kan ƙudurin da ya yi, sai ya koma ga Ubangijinsa ya miƙa masa dukkan al’amuransa, ya kuma roƙi gafararsa ya kuma nemi ya ba shi wani mulki na musamman da zai keɓance shi da shi, wanda bai kamaci wani mutum a bayansa ya sami irinsa ba, domin Allah shi ne mai yawan baiwa mai yawan kyauta.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle daren jiya wani ifritu daga cikin aljannu ya yiwo kaina domin ya yanke mini salla, sai Allah ya ba ni dama a kansa har na so in ɗaure shi a jikin ɗaya daga dirkokin masallaci domin ku wayi gari ku duka ku gan shi, sai na tuna addu’ar ɗan’uwana Sulaiman inda ya ce: “Ya Ubangijina, ka gafarta mini kuma ka ba ni mulki wanda bai kamaci wani mutum bayana ya sami irinsa ba....” [Bukhari #4308 da Muslim #541].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Yayin da Sulaimanu ɗan Dawud ya gama ginin Baitil Maƙdis sai ya roƙi Allah abubuwa uku: Ya roƙi Allah ya ba shi hukunci wanda zai dace da hukuncinsa, sai aka ba shi; ya kuma roƙe shi ya ba shi mulki wanda bai kamaci wani mutum ya sami irinsa a bayansa ba, aka ba shi; ya roƙe shi bayan ya gama gina masallaci cewa dukkan

mutumin da ya zo gare shi ba don komai ba sai don ya yi salla a cikinsa, to kar ya fita daga cikinsa har sai ya wanke masa laifukansa kamar ranar da mahaifiyarsa ta haife shi." [Nasa'i #693 da Ahmad #6644 da Ibn Majah #1408].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa masa, ya kuma yi masa wasu manya-manyan ni'imomi waɗanda suka haɗa da:
Na ɗaya, ya hore masa iska mai tafiya da umarninsa a cikin nutsuwa duk kuwa da ƙarfin kaɗawarta da kuma saurinta, takan ɗauke shi ta kai shi duk inda yake so.
Na biyu, ya hore masa shaiɗanu masu bin umarninsa, daga cikinsu akwai magina da suke yi masa kowane irin gini yake so; akwai kuma masu nutso a cikin kogi suna fito masa da lu'u-lu'u da murjani da sauran duwatsun cikin ruwa masu daraja.
Na uku, wasu kuma shaiɗanu ne masu taurin kai, su kuma an ba shi iko a kansu, don haka ya sa aka ɗaure su a cikin maruruwa ba sa iya motsawa nan da can.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa cewa ya danƙa masa wannan gawurtaccen mulki da wannan baiwa mai girma, ya kuma ba shi izinin ya sarrafa ta yadda ya ga dama; ya ɗauki abin da ya ga dama daga arzukin da Allah ya yi masa a masarautarsa ya ba wa wanda ya ga damar ba wa, ya kuma hana wanda ya ga damar hana wa, babu wanda zai bincike shi a kan haka.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabe shi da cewa lalle shi yana daga cikin makusanta a wurinsa yana da kuma kyakkyawar makoma watau Aljanna. Don haka kamar yadda ya yalwata masa a nan duniya to hakanan ma a lahira zai yi masa kyakkyawan sakamako.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya yi haƙuri a kan wata cuta da ta same shi, to Allah zai yi masa kyakkyawan sakamako duniya da lahira.

2. Yana daga cikin ladabi ga Allah bawa ya danganta duk abu marar kyau da zai same shi zuwa ga Shaiɗan ba ga Allah ba, tare da cewa komai gaba ɗaya mai daɗi da marar daɗi, duk halittar Allah ne.

3. Cuta tana kama annabawan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Wannan ya tabbatar da cewa su ba sa mallaka wa kansu wani amfani ko wata cutarwa sai abin da Allah ya hukunta musu.

4. Yana daga cikin hanyoyin komawa ga Allah, bawa ya yi tawassuli da wani mawuyacin halin da yake ciki don Allah ya kawo masa ɗauki cikin gaggawa.

5. Girman Kudurar Allah ta fitar da ruwa daga ƙasa bayan an haure ta.

6. Idan bawa ya yi haƙuri a kan wani bala'i da Allah ya saukar masa, sai ya musanya masa da ninkin abin da ya rasa.

7. Masu hankali ne kaɗai suke wa'azantuwa da abin da yake cikin labarai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake bayarwa na annabawa da al'ummun da suka gabata.

8. Amfani da wata dabara da shari'a ta yarda da ita don kuɓuta daga faɗawa cikin abin da ya fi ƙarfin mutum. Kamar wanda zai yi rantsuwa sai ya yi wa ɗansa ko almajirinsa bulala ɗari, to sai a ce ya ɗauki tsintsiya mai tsinke ɗari ya dake shi da ita. To daga nan ya warware rantsuwarsa.

9. Zamantowar mutum bawa ga Allah mai bauta masa, wani babban matsayi ne da manyan bayin Allah suke tiŋkaho da shi.

10. Falalar mai haƙuri a kan musibar da ta same shi da komawa ga Allah.

Suratu Sad (41-44)

وَٱذۡكُرۡ عَبۡدَنَآ أَيُّوبَ إِذۡ نَادَىٰ رَبَّهُۥٓ أَنِّي مَسَّنِيَ ٱلشَّيۡطَٰنُ بِنُصۡبٖ وَعَذَابٍ ۝٤١ ٱرۡكُضۡ بِرِجۡلِكَۖ هَٰذَا مُغۡتَسَلُۢ بَارِدٞ وَشَرَابٞ ۝٤٢ وَوَهَبۡنَا لَهُۥٓ أَهۡلَهُۥ
وَمِثۡلَهُم مَّعَهُمۡ رَحۡمَةٗ مِّنَّا وَذِكۡرَىٰ لِأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ۝٤٣ وَخُذۡ بِيَدِكَ ضِغۡثٗا فَٱضۡرِب بِّهِۦ وَلَا تَحۡنَثۡۗ إِنَّا وَجَدۡنَٰهُ صَابِرٗاۚ نِّعۡمَ ٱلۡعَبۡدُ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٞ ۝٤٤

41. Ka kuma tuna bawanmu Ayyuba lokacin da ya kira Ubangijinsa (yana cewa): “Lalle ni Shaiɗan ya shafe ni da wata wahala da azaba.” |

42. (Aka ce da shi): “Ka hauri ƙasa da ƙafarka; (sai ruwa ya ɓuɓbugo, aka ce da shi): “Wannan ruwan wanka ne mai sanyi da na sha.”

43. Muka kuma yi masa baiwar iyalinsa da kuma (ƙarin) wasu kamarsu (na `ya`ya da jikoki) don jin ƙai daga gare Mu da kuma wa’azi ga masu hankula.

44. Ka ɗauki danƙi na ciyawa da hannunka ka bugi (matarka da shi), kada ka karya rantsuwarka. Lalle Mun same shi mai haƙuri. Madalla da wannan bawan; lalle shi mai yawan komawa ne (ga Allah).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tana tunatar da Annabi (ﷺ) labarin bawansa Annabi Ayyub (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da ya kamu da wata matsananciyar rashin lafiya, amma ya yi haƙuri ya jure bai koka wa wani abin da yake ciki ba sai Allah, yayin da ya yi addu’a ya roƙe shi cewa, Shaiɗan ya shafe shi da wata cuta mai wahalarwa da azabtarwa. Ya kuma rasa iyalansa da dukiyarsa bayan ya kasance mutum mai yawan dukiya. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa masa roƙonsa ya umarce shi da ya hauri ƙasa da ƙafarsa. Da ya aikata hakan sai ruwa ya ɓuɓbugo daga cikinta wanda ya riƙa sha yana wanka da shi har cutar da ke tare da shi ta gushe.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya amsa addu’ar Annabi Ayyuba ya kuma yaye masa duk cutar da take damun sa, ya kuma dawo masa da madadin iyalansa waɗanda ya rasa, har ya ƙara masa yawan ‘ya’ya da jikoki don yalwata jin ƙan Allah gare shi. Wannan kuma sakamakon haƙurin da ya yi ne, kuma saboda mutane masu hankali su wa’azantu su gane cewa mahaƙurci mawadaci ne.
Duk da halin da Annabi Ayyuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake ciki sai da matarsa ta fusata shi har ya rantse da Allah cewa sai ya yi mata bulala ɗari. A kan haka sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya ɗauki danƙi na ciyawa da hannunsa ya bugi matarsa da shi don ya warware rantsuwarsa ba tare da ya karya ta ba. Sai ya aikata kamar yadda aka umarce shi, don haka bai yi kaffara ba. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabe shi da cewa ya same shi mutum mai haƙuri a kan bala’in da ya auka masa, kuma madalla da bawan Allah Ayyuba (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), lalle tabbas shi mutum ne mai yawan komawa ga Allah mai yawan tuba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yabon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga annabawansa Ibrahimu da Is’haƙa da Ya’aƙubu da cewa, su masu ƙarfi ne wajen ibada, masu basira ne a addini.

2. Mafi darajar mutane a wurin Allah su ne masu ƙarfi wajen bautar Allah da zartar da umarninsa, kuma masu ƙarfin basira wajen fahimtar addininsa.

3. Babbar baiwa ce da Allah zai yi wa bawansa ya sanya shi mai tunawa da lahira koyaushe.

4. Yabon Allah ga annabawansa, watau Isma'ila da Alyasa'u da Zulkifli, dukkansu zaɓaɓɓu ne a wurinsa.

Suratu Sad (45-48)
وَٱذۡكُرۡ عِبَٰدَنَآ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ أُوْلِي ٱلۡأَيۡدِي وَٱلۡأَبۡصَٰرِ ٤٥ إِنَّآ أَخۡلَصۡنَٰهُم بِخَالِصَةٖ ذِكۡرَى ٱلدَّارِ ٤٦ وَإِنَّهُمۡ عِندَنَا لَمِنَ ٱلۡمُصۡطَفَيۡنَ ٱلۡأَخۡيَارِ ٤٧ وَٱذۡكُرۡ إِسۡمَٰعِيلَ وَٱلۡيَسَعَ وَذَا ٱلۡكِفۡلِۖ وَكُلّٞ مِّنَ ٱلۡأَخۡيَارِ ٤٨

45. Ka kuma tuna bayinmu Ibrahimu da Is'haƙa da Yaƙubu ma'abota ƙarfi da basira.

46. Lalle Mun keɓance su da wata keɓantacciyar ɗabi'a, (ita ce) tuna lahira.

47. Kuma lalle su a wurinmu tabbas suna daga cikin zaɓaɓɓu nagari.

48. Ka kuma tuna Isma'ila da Alyasa'u da Zulkifli; dukkaninsu kuma suna cikin zaɓaɓɓu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙara tunatar wa Annabi (ﷺ) labarin bayinsa kuma manzanninsa zaɓaɓɓu da ya aika su cikin al'ummunsu, watau su ne Ibrahim da Is'haƙa da Ya'ƙubu, dukkansu sun zamanto ma'abota ƙarfi ne wajen bautar Allah da neman yardarsa kuma masu basira ne game da addinin Allah da fahimtar gaskiya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu wata baiwa ta musamman da ya keɓance su da ita, watau ya raya musu zukatansu da tunanin lahira da yi mata tanadin aiki nagari da kiran mutane zuwa ga kyakkyawan aiki domin zuwan wannan rana.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, su waɗannan annabawa suna daga cikin bayinsa da ya zaɓo domin su bauta masa su yi masa biyayya, ya kuma zaɓe su ya ba su manzanci zuwa ga mutane domin su isar musu da saƙonsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tunantar da Annabi (ﷺ) labarin Annabi Isma'ila ɗan Annabi Ibrahim da labarin Annabi Alyasa'u da na Annabi Zulkifli; ya yi musu kyakkyawan yabo domin dukkansu suna cikin bayinsa zaɓaɓɓu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani ɗaukaka ce ga waɗanda suka yi kyakkyawan riƙo da koyarwarsa.

2. Falalar taƙawa da waɗanda suka siffanta da ita.

3. Ni'imar lahira mai ɗorewa ce, ba ta yankewa kamar yadda 'yan Aljanna ba za su mutu ba.

Suratu Sad (49-54)
هَٰذَا ذِكۡرٞۚ وَإِنَّ لِلۡمُتَّقِينَ لَحُسۡنَ مَـَٔابٖ ٤٩ جَنَّٰتِ عَدۡنٖ مُّفَتَّحَةٗ لَّهُمُ ٱلۡأَبۡوَٰبُ ٥٠ مُتَّكِـِٔينَ فِيهَا يَدۡعُونَ فِيهَا بِفَٰكِهَةٖ كَثِيرَةٖ وَشَرَابٖ ٥١ وَعِندَهُمۡ قَٰصِرَٰتُ ٱلطَّرۡفِ أَتۡرَابٌ ٥٢ هَٰذَا مَا تُوعَدُونَ لِيَوۡمِ ٱلۡحِسَابِ ٥٣ إِنَّ هَٰذَا لَرِزۡقُنَا مَا لَهُۥ مِن نَّفَادٍ ٥٤

49. Wannan kyakkyawan ambato ne (a gare su). Kuma lalle masu taƙawa tabbas suna da kyakkyawar makoma.

50. (Wato) gidajen Aljannar dawwama, alhali ƙofofi suna buɗe saboda su.

51. Suna kishingiɗe a cikinsu, suna kiran a kawo musu ababen marmari masu yawa da abin sha a cikinsu.

52. Kuma a wurinsu akwai tsaraikun mata masu taƙaita kallo (ga mazansu kawai).

53. Wannan shi ne ake yi muku alƙawari da shi a ranar hisabi.

54. Lalle wannan tabbas arzikinmu ne ba mai ƙarewa ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa waɗancan annabawa da suka gabata, sun samu kyakkyawan ambato ne a cikin littafinsa mai girma, watau Alƙur'ani, wanda yake wata ɗaukaka ce a gare su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk bayinsa waɗanda suka kiyaye dokokinsa; suka yi aiki da umarninsa suka kuma guji haninsa, to suna da kyakkyawar makoma a lahira, watau gidajen Aljanna na zama dindindin a ranar alƙiyama; za su iske ƙofofinsu a buɗe don yi musu kyakkyawar tarba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin ni'imar da ya tanadar musu a Aljanna, da cewa za su zamanto masu kishingiɗa a kan gadajen da aka yi wa kwalliya ta alfarma, suna kiran masu yi musu hidima don su kawo musu duk abin da suke sha'awa na kayan marmari iri-iri na ci da na sha, kamar giyar Aljanna da madara da zuma da sauransu. An kuma shirya mata tsareku a shekaru masu taƙaita kallonsu ga mazajensu, ba sa kallon wasu mazajen daban.
Allah kuma ya tabbatar da cewa wannan sakamako da aka ambata da ma can an tanade shi ne a ranar alƙiyama saboda masu taƙawa da kiyaye dokokin Allah, don kyawawan ayyukan da suka yi a duniya. Kuma arziki ne mai ɗorewa ba zai yanke ba har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kyakkyawan salon wa'azin Alƙur'ani shi ne idan ya yi maganar Aljanna sai kuma ya kawo maganar 'yan wuta, ko kuma akasi, domin ya haɗa matsayin kwaɗaitarwa da na tsoratarwa. Haka ne ya dace masu kira zuwa ga Allah su yi.

2. Yadda za a ni'imta `yan Aljanna da dangogin ni'ima iri-iri, hakanan su ma 'yan wuta za a yi musu azaba da nau'o'in azaba daban-daban.

3. Tabbatar da cewa mabiya da shugabanninsu na ɓata za su yi baram-baram da juna a ranar alƙiyama, kowa zai la'anci ɗan'uwansa, babu wanda kuma zai iya taimakon wani.

4. 'Yan wuta za a ba su dama su riƙa magana da junansu a cikin wuta duk kuwa da irin tsananin azabar da suke sha.

5. 'Yan wuta za su riƙa tuna rashin mutuncin da suka riƙa yi wa muminai a duniya da kalaman ɓatanci da suka riƙa faɗa musu.

6. Kafirai sun kasance suna yi wa muminai kallon ɓatattu waɗanda ko alƙiyama ta tsaya su wuta Allah zai jefa su.

Suratu Sad (55-64)

هَٰذَاۚ وَإِنَّ لِلطَّٰغِينَ لَشَرَّ مَـَٔابٍ ۝٥٥ جَهَنَّمَ يَصۡلَوۡنَهَا فَبِئۡسَ ٱلۡمِهَادُ ۝٥٦ هَٰذَا فَلۡيَذُوقُوهُ حَمِيمٞ وَغَسَّاقٞ ۝٥٧ وَءَاخَرُ مِن شَكۡلِهِۦٓ أَزۡوَٰجٌ ۝٥٨ هَٰذَا فَوۡجٞ مُّقۡتَحِمٞ مَّعَكُمۡ لَا مَرۡحَبَۢا بِهِمۡۚ إِنَّهُمۡ صَالُواْ ٱلنَّارِ ۝٥٩ قَالُواْ بَلۡ أَنتُمۡ لَا مَرۡحَبَۢا بِكُمۡۖ أَنتُمۡ قَدَّمۡتُمُوهُ لَنَاۖ فَبِئۡسَ ٱلۡقَرَارُ ۝٦٠ قَالُواْ رَبَّنَا مَن قَدَّمَ لَنَا هَٰذَا فَزِدۡهُ عَذَابٗا ضِعۡفٗا فِي ٱلنَّارِ ۝٦١ وَقَالُواْ مَا لَنَا لَا نَرَىٰ رِجَالٗا كُنَّا نَعُدُّهُم مِّنَ ٱلۡأَشۡرَارِ ۝٦٢ أَتَّخَذۡنَٰهُمۡ سِخۡرِيًّا أَمۡ زَاغَتۡ عَنۡهُمُ ٱلۡأَبۡصَٰرُ ۝٦٣ إِنَّ ذَٰلِكَ لَحَقّٞ تَخَاصُمُ أَهۡلِ ٱلنَّارِ ۝٦٤

55. Wannan (shi ne sakamakon masu taƙawa). Kuma lalle masu ɗagawa tabbas suna da mummunar makoma.

56. (Wato) Jahannama wadda za su shige ta, to wannan shimfiɗar zama ta munana.

57. Wannan (sakamako ne), sai su ɗanɗane shi na tafasasshen ruwa da mugunya.

58. Da kuma wani mai kama da shi iri daban-daban.

59. (Za a ce da su): “Wannan ma wani gungun ne (na mabiya) mai afkawa tare da ku;” (sai shugabannin su ce): “Ba ma yin maraba da su.” Lalle (su duka) wuta za su shiga.

60. (Mabiyan kuma sai) su ce: “A’a, ku dai ne ba ma maraba da ku; ku ne kuka kawo mana shi (wannan mummunan sakamako);” to wannan matabbata ta munana.

61. Sai suka ce: “Ya Ubangijinmu, duk wanda ya kawo mana wannan (sakamakon) to Ka ƙara masa ninkin azaba a cikin wuta.”

62. Suka kuma ce: “Me ya sa ne ba ma ganin wasu mazaje da muka kasance muna lissafa su cikin ashararai?

63. “Shin mun ɗauke su ne ababen yi wa ba’a (a duniya), ko kuwa idanuwanmu ne suka bauɗe ba sa hango su?”

64. Lalle wannan jayayyar ta ‘yan wuta gaskiya ce.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa abubuwan da suka gabata an tanade su ne don masu taƙawa. To amma masu ƙetare iyakokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta hanyar rungumar kafirci da saɓon Allah, su kuma suna da mummunar makoma a ranar alƙiyama. Sakamakonsu ita ce wutar Jahannama da za su shige ta ta kewaye su ta ko’ina su ɗanɗani zafinta, ta zame musu tamkar shimfiɗa. Tir da wannan shimfiɗa tasu, watau Jahannama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana dangogin azabar da za su ɗanɗana a wutar, bayan tsananin zafinta, abin shansu shi ne tafasasshen ruwa da kuma ruwan mugunyar da yake zuba daga jikin ‘yan wuta. Ba su da wani abin sha sai wannan mummunan ruwan wanda ba ya kashe ƙishi. Akwai kuma wasu dangogi na azaba iri-iri da za a yi ta yi musu wanda ba sa yankewa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa idan ‘yan wuta suka shiga wuta sai rigima ta kaure tsakaninsu, su shiga nesanta kansu da juna, ta hanyar la’antar junansu; wasu su ce wa wasu, waɗannan ma wata ƙungiya ce ta ‘yan wuta da za su shiga wuta tare da su, sai su kuma su amsa musu da cewa ba sa maraba da su, domin su ma za su ɗanɗani irin azabar da waɗancan suke ɗanɗana.

Sai gungun mabiyan su mayar wa shugabanninsu martani da cewa su ma ba sa maraba da su, domin su ne sanadiyyar samun kansu a cikin wannan mummunar azaba, saboda su ne suka ɓatar da su, don haka sai su yi tir da wannan matabbata, watau wutar Jahannama, wadda za su yi tarayya ta zama a cikinta har abada.
Sai mabiyan su kuma su ci gaba da roƙon Allah da cewa, duk wanda ya yi sanadiyyar ɓatansu a duniya har suka kauce wa hanyar shiriya, to su ma Allah ya ninninka musu azabar wuta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda maƙiya Allah za su shiga tattaunawa a cikin wutar Jahannama game da muminai waɗanda suka riƙa yi wa izgili a duniya, suna yi musu kallon wasu ɓatattu, sai kuma ga shi ba su gan su a cikin wuta ba, sai su riƙa tambayar junansu cewa, me ya sa ne ba sa ganin wasu mutane da tun a duniya suna lissafa su a cikin ashararai waɗanda suka cancanci azabtarwa? Sai su yi mamakin rashin ganin su a wuta, suna tambayar junansu cewa, ashe wai da man izgili da ba'ar da suke yi musu bisa kuskure ne, ko kuma daidai ne, idanuwansu ne kawai suka bauɗe ba sa iya hango su a cikin wutar?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa, wannan labari da ya ba shi na rigimar 'yan wuta a junansu bayan sun shige ta, tabbas gaskiya ne babu wani kokwanto a cikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da annabcin Manzon Allah (ﷺ) da kuma Kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Girman lamarin Alƙur'ani wanda ya ƙunshi manya-manyan labarai da suka danganci Kaɗaitakar Allah da labaran annabawan Allah, da kuma zuwan ranar lahira da abubuwan da za su faru a cikinta.

3. Tabbatar da dalilan ingancin annabcin Manzon Allah (ﷺ), domin yana ba da labarin abubuwan da, a da ba shi da wata masaniya a kansu kamar labarin tattaunawar mala'iku da Ubangijinsu game da sha'anin halittar Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

4. Annabi Muhammadu (ﷺ) bai san gaibu ba sai abin da Allah ya sanar da shi ta hanyar wayahi.

5. Tabbatar da samuwar mala'iku masu girman daraja a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Sad (65-70)
قُلْ إِنَّمَآ أَنَا۠ مُنذِرٌ ۖ وَمَا مِنْ إِلَٰهٍ إِلَّا ٱللَّهُ ٱلْوَٰحِدُ ٱلْقَهَّارُ ﴿٦٥﴾ رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا ٱلْعَزِيزُ ٱلْغَفَّارُ ﴿٦٦﴾ قُلْ هُوَ نَبَؤٌا۟ عَظِيمٌ ﴿٦٧﴾ أَنتُمْ عَنْهُ
مُعْرِضُونَ ﴿٦٨﴾ مَا كَانَ لِىَ مِنْ عِلْمٍۭ بِٱلْمَلَإِ ٱلْأَعْلَىٰٓ إِذْ يَخْتَصِمُونَ ﴿٦٩﴾ إِن يُوحَىٰٓ إِلَىَّ إِلَّآ أَنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٧٠﴾

65. Ka ce: "Ni dai mai gargaɗi ne kawai; kuma babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Allah Ɗaya, Mai rinjaye.

66. "Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, Mabuwayi, Mai gafara."

67. Ka ce: "Shi (wannan Alƙur'ani) labari ne mai girma.

68. "Da kuke bijire masa.

69. "Ban zama na san wani abu ba dangane da mala'iku masu daraja lokacin da suke yin muhawara (game da halittar Adamu).

70. “Ba wani wahayi da aka yiwo min sai kawai cewa ni mai gargaɗi ne mai bayyanawa.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya faɗa wa mutanensa kafirai cewa, shi fa kawai ya zo ne don ya yi musu gargaɗi game da azabar Allah kada ta auka musu saboda kafircinsu da ƙaryata Manzonsa da suke yi, kuma ya tabbatar musu da cewa babu wani wanda ya cancanci a bauta masa sai Allah shi kaɗai; shi ne makaɗaici a girmansa da sunayensa da siffofinsa da ayyukansa; mai rinjaye da galaba a kan komai. Shi ne kuma Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu; shi ne mahaliccinsu mai gudanar da lamuransu yadda ya ga dama; dukkansu bayinsa ne, shi ne kuma mabuwayi cikin mulkinsa, babu mai iya ja da shi; shi ne kuma mai gafarta wa bayinsa zunubansu idan sun tuba sun nemi gafararsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar Manzonsa (ﷺ) ya tabbatar wa kafirai cewa, Alƙur’ani labari ne mai girman sha’ani, amma kuma sai ga su suna bijire masa.
Sai kuma Allah ya sake umartar Manzonsa da ya shaida wa kafirai cewa, ba shi da wata masaniya game da muhawarar da ta kasance tsakanin mala’iku lokacin da suke tattaunawa game da halittar Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da sauko da shi bayan ƙasa. Ba don Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da shi ba da ba zai san komai a kai ba. Don haka ya shaida musu cewa shi fa kawai ana yi masa wahayi ne a kan ya yi wa mutanensa gargaɗi game da azabar Allah kada ta auka musu, ya kuma bayyana gargaɗinsa a fili. Wannan kuwa dalili ne mai tabbatar da annabcinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittar ɗan’adam na farko, watau Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga taɓo.

2. Babban matsayi da martaba da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan’adam yayin da ya halicci Annabi Adamu da hannunsa mai daraja ya kuma busa masa ruhinsa ya kuma umarci mala’iku su yi masa sujjada.

3. Biyayyar mala’iku ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Girman kai da hassada su ne musabbabin hallakar Iblis da taɓewarsa.

5. Kafa hujja da tsantsar hankali domin kawar da tabbataccen nassi daga Allah, hanya ce ta Iblis wadda ta kai shi ga hallaka.

6. Tabbatar da siffar hannaye biyu ga Allah kamar yadda ya dace da girmansa ba tare da kwatance ba.

7. Iblis ba shi da ikon ɓatar da zaɓaɓɓun bayin Allah masu tsarkake bautarsu gare shi.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin cika wutar Jahannama da Iblis shi da mabiyansa.

Suratu Sad (71-85)
إِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّي خَٰلِقٌۢ بَشَرًا مِّن طِينٍ ﴿٧١﴾ فَإِذَا سَوَّيْتُهُۥ وَنَفَخْتُ فِيهِ مِن رُّوحِي فَقَعُواْ لَهُۥ سَٰجِدِينَ ﴿٧٢﴾ فَسَجَدَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ كُلُّهُمْ
أَجْمَعُونَ ﴿٧٣﴾ إِلَّآ إِبْلِيسَ ٱسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٧٤﴾ قَالَ يَٰٓإِبْلِيسُ مَا مَنَعَكَ أَن تَسْجُدَ لِمَا خَلَقْتُ بِيَدَيَّۖ أَسْتَكْبَرْتَ أَمْ كُنتَ مِنَ
ٱلْعَالِينَ ﴿٧٥﴾ قَالَ أَنَا۠ خَيْرٌ مِّنْهُ خَلَقْتَنِي مِن نَّارٍ وَخَلَقْتَهُۥ مِن طِينٍ ﴿٧٦﴾ قَالَ فَٱخْرُجْ مِنْهَا فَإِنَّكَ رَجِيمٌ ﴿٧٧﴾ وَإِنَّ عَلَيْكَ لَعْنَتِيٓ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلدِّينِ ﴿٧٨﴾

قَالَ رَبِّ فَأَنظِرۡنِيٓ إِلَىٰ يَوۡمِ يُبۡعَثُونَ ٧٩ قَالَ فَإِنَّكَ مِنَ ٱلۡمُنظَرِينَ ٨٠ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡوَقۡتِ ٱلۡمَعۡلُومِ ٨١ قَالَ فَبِعِزَّتِكَ لَأُغۡوِيَنَّهُمۡ أَجۡمَعِينَ ٨٢ إِلَّا عِبَادَكَ مِنۡهُمُ ٱلۡمُخۡلَصِينَ ٨٣ قَالَ فَٱلۡحَقُّ وَٱلۡحَقَّ أَقُولُ ٨٤ لَأَمۡلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنكَ وَمِمَّن تَبِعَكَ مِنۡهُمۡ أَجۡمَعِينَ ٨٥

71. (Ka tuna) lokacin da Ubangijinka Ya ce da mala'iku: "Lalle Ni zan halicci wani mutum daga taɓo.

72. "To idan Na daidaita shi Na kuma busa masa ruhina, sai ku faɗi kuna masu yi masa sujjada."

73. Sai mala'iku dukkaninsu gaba ɗaya suka yi sujjada.

74. Sai Iblisa da ya yi girman kai ya kuma zama cikin kafirai.

75. (Allah) Ya ce: "Ya kai Iblisa, me ya hana ka yin sujjada ga abin da Na halitta da hannayena biyu? Ka yi girman kai ne, ko kuwa da man can ka kasance daga masu nuna isa?"

76. Sai ya ce: "Ni ai na fi shi; (domin) Ka halicce ni ne daga wuta, (shi) kuma Ka halicce shi daga taɓo."

77. (Sai Allah) Ya ce (da shi): "To ka fice daga cikinta (wato Aljanna) saboda kai lalle korarre ne (daga rahama).

78. "Kuma lalle la'antata tabbas ta hau kanka har zuwa ranar alƙiyama."

79. (Sai Iblisa) ya ce: "Ya Ubangijina, Ka saurara min har zuwa ranar da za a tashe su."

80. (Sai Allah) Ya ce: "To lalle kana cikin waɗanda za a saurara wa.

81. "Har zuwa ranar lokaci sananne."

82. Sai ya ce: "To na rantse da girmanka tabbas zan ɓatar da su baki ɗaya.

83. "Sai dai bayinka waɗanda aka tsarkake daga cikinsu."

84. (Allah) Ya ce: "Gaskiya (daga gare Ni take), kuma gaskiyar kawai Nake faɗa!

85. "Tabbas zan cika Jahannama da kai da kuma waɗanda suka bi ka baki ɗaya."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da Annabi (ﷺ) lokacin da ya faɗa wa mala'iku cewa zai halici mutum da taɓo, watau Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya kuma umarce su da cewa idan ya gama daidaita halittarsa, ya kuma busa masa ruhinsa, to dukkansu su faɗi su yi masa sujjada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa, mala'iku sun bi wannan umarni nasa, sun faɗi sun yi wa Annabi Adamu sujjada ta girmamawa, ba kuma wanda bai yi sujjadar ba sai Iblis kaɗai, shi ne girman kai ya hana shi bin wannan umarni na Allah sai ya tabbata daga cikin kafirai.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi Iblis cewa, me ya hana shi yin sujjada ga Annabi Adamu wanda shi ne ya halicce shi da hannayensa biyu? Shin girman kansa ne da yake nuna wa Annabi Adamu ko kuwa da man can yana nuna isa da jin kai ne ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka)? Sai Iblis ya amsa wa Allah da cewa, shi ai fa ya fi Annabi Adamu, domin an halicce shi ne da wuta, Annabi Adamu kuwa da taɓo aka halicce shi,

don haka yana ganin wuta ta fi tabo daraja, saboda haka shi ya fi Annabi Adamu daraja, shi ya sa ya ƙi yi masa sujjada.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Iblis da ya fice daga gidan Aljanna a matsayin korarre. Kuma la'anar Allah ta tabbata a kansa har zuwa ranar alƙiyama, don haka ba shi ba gidan Aljanna har abada.
To sai Iblis ya nemi wata alfarma a wajen Allah da ya saurara masa kada ya kashe shi har zuwa lokacin da zai tashi bayinsa domin hisabi. Sai ko Allah ya bayyana masa cewa ya ba shi abin da ya nema, ya saurara masa har zuwa wani iyakantaccen lokaci sananne wanda a cikinsa zai karɓi ransa.
Daga nan sai Iblis ya yi rantsuwa da ikon Allah da Izzarsa cewa lalle sai ya ɓatar da zurriyar Annabi Adamu kakaf, in ban da bayin Allah da ya tsarkake su ya tsare su daga faɗawa cikin tarkonsa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa daga gare shi gaskiya take, kuma tsantsar gaskiya kawai yake faɗa, cewa kada Iblis ya ji da wai, tabbas sai ya cika Jahannama da shi da duk waɗanda suka bi shi a kan kafirci daga cikin zurriyar Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne mai kira zuwa ga Allah ya guje wa nuna kwaɗayinsa a kan abin hannun mutane domin da'awarsa ta yi tasiri.

2. Haramun ne ga mutum ya riƙa kallafa wa kansa faɗar abin da ba shi da ilimi a kansa, ko ya ɗora wa kansa ibadar da ta fi ƙarfinsa.

3. Ɗan'adam bayan ya mutu zai gane gaskiyar abin da annabawa suka zo masa da shi.

Suratu Sad (86-88)

قُلْ مَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُتَكَلِّفِينَ ﴿٨٦﴾ إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿٨٧﴾ وَلَتَعْلَمُنَّ نَبَأَهُۥ بَعْدَ حِينٍۭ ﴿٨٨﴾

86. Ka faɗa (musu): "Babu wani lada da nake tambayar ku game da shi, (wato isar da aike), kuma ni ba na cikin masu matsa wa kai (don in ƙago wani sabon saƙo).

87. "Shi ba wani abu ba ne in ban da tunatarwa ga talikai.

88. "Kuma tabbas za ku san gaskiyar labarinsa (watau Alƙur'ani) bayan wani ɗan lokaci."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya shaida wa mushirikai cewa, ba ya neman su biya shi wani lada a kan saƙon Allah da yake isar musu da nasihar da yake yi musu, kuma har ila yau shi ba ya matsa wa kansa sai ya kawo wani ƙarin umarni a kan wanda aka yi masa, yana tsaye ne kyam a kan abin da aka yi masa wahayi da shi ba daɗi ba ragi. Kuma su sani cewa, shi Alƙur'ani tunatarwa ce ga talikai mutane da aljannu, kuma lalle tabbas za su san gaskiyar labarin wannan Alƙur'ani su gane cewa daga Allah ne da zarar sun mutu sun koma ga mahaliccinsu Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kamalar Alƙur'ani da kuma girmansa, domin shi saukakke ne daga Allah Mabuwayi mai hikima. Don haka shi maganar Allah ce kuma siffarsa ce; kamar yadda yake cikakke ta kowace fuska, to hakanan maganarsa, watau Alƙur'ani yake cikakke ta kowace fuska.

2. Darajar Annabi Muhammadu (ﷺ) da ɗaukakarsa, domin shi ne aka saukar wa littafin da ya fi kowane littafi daraja da ɗaukaka a bayan ƙasa.

3. Duk abin da Alƙur'ani ya ƙunsa na labarai da hukunce-hukunce da aƙidu gaskiya ne babu kokwanto a cikinsu. Hakanan duk abin da ya saɓa masa ƙarya ne ba gaskiya ba.

4. Kamalar addinin Musulunci, domin shi addini ne tatacce wanda babu shirka ko kaɗan a cikinsa. Kuma shi ne addinin da Allah ya zaɓa wa mafificin halittarsa Annabi Muhammadu (ﷺ), ya kuma umarce shi da ya bauta masa ba tare da haɗa shi da komai ba.

5. Dukkan nau'o'in bauta na Allah ne shi kaɗai, bai halatta a nufi wani da su ba.

6. Mushirkan Larabawa waɗanda suka riƙi gumaka suna bauta musu ba Allah ba, ba suna bauta musu ne don sun ɗauka su ne suka yi halitta ba; suna bauta musu ne domin suna ganin wai su ne suka fi su kusanci da Allah, don haka za su riƙe su a matsayin tsani zuwa gare shi, don ya biya musu buƙatunsu kuma su sami cetonsu a wurinsa. Da haka ne suka saki Tauhidi suka rungumi shirka.

7. Duk wanda ya mayar da ƙarya ta zama ɗabi'arsa ya kuma siffantu da kafirci, to Allah zai doɗe zuciyarsa, sai shiriya ta ƙi shiga cikinta sakamakon munanan ayyukansa.

39-Suratuz Zumar

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna '*Suratuz Zumar*' saboda a cikinta ne kaɗai wannan kalmar ta zo, watau '*Zumar'*.
Tana nufin ƙungiyoyi.
Wannan suna ya zo cikin hadisin A'isha, (Allah ya kara mata yarda), wanda Tirmizi ya ruwaito. [Dubi, Tirmizi #3405].
Wahab ɗan Munabbih ya kira ta da suna *Suratul Ghuraf*. [Suyuɗi, *Addurrul-Mansur*, Juzu'i na 12, Shafi na 736].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai sun haɗu a kan cewa Sura ce *Makkiyya.* An ruwaito daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) cewa daga aya ta 53 zuwa ta 55 sun sauka ne a Madina. Amma maganar farko ce ta fi inganci, watau dukkanta *Makkiyya* ce.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta hamsin da tara (59) a jerin saukar surorin Alƙur'ani bisa ingantacciyar magana, ta sauka bayan '*Suratus Saba'i*' gabanin '*Suratu Ghafir*'.

4. Adadin ayoyinta:
A lissafin mutanen Kufa adadin ayoyinta saba'in da biyar ne (75). A wajen mutanen Sham kuwa adadinsu saba'in da uku ne (73). A wurin mutanen Madina da Makka da Basra su saba'in da biyu ne (72).

5. Falalarta:
An karƀo daga A'isha, (Allah ya kara mata yarda) ta ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya kasance ba ya barci har sai ya karanta *Suratuz Zumar* da *Suratu Bani Isra'il*." [Tirmizi #3405 da Ahmad #24388].

6. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne, tabbatar da Kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da rushe shirka da bautar wanin Allah, ta hanyar nuni zuwa ga dalilai masu ƙarfi na hankali da za a iya ganin su a halittun Allah na sama da na ƙasa.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tabbatar da Kaɗaitakar Allah da rushe shirka.
• Rushe hujjojin mushirikai na yin shirka da Allah wajen bauta.
• Dalilai masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah waɗanda suka haɗa da Kaɗaitakarsa wajen halittar sammai da ƙasa da abubuwan da suke cikinsu; da gudanar da su a kan cikakken tsari wanda kowa yake gani babu mai musu da hakan.
• Abubuwan mamaki da suke cikin matakan halittar mutum da dabba.

• Kira zuwa ga mushrikai kan su yi tuntuntuni game da butulce wa ni’imar Allah da suke yi, saɓanin muminai masu kaɗaita Allah.
• Bayani a kan cewa addinin kaɗaita Allah da bauta shi ne abin da duk annabawan Allah suka zo da shi.
• Gargaɗi ga mushirikai a kan su guji aikata abin da zai jawo musu hallaka, kamar yadda aka hallaka al’ummun da suka gabace su.
• Tabbatar da aƙidar tashi bayan mutuwa da tsayuwar alƙiyama da sakamakon Aljanna ga muminai da na wuta ga kafirai.

Suratuz Zumar (1-4)
تَنزِيلُ ٱلۡكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَكِيمِ ١ إِنَّآ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ فَٱعۡبُدِ ٱللَّهَ مُخۡلِصٗا لَّهُ ٱلدِّينَ ٢ أَلَا لِلَّهِ ٱلدِّينُ ٱلۡخَالِصُۚ وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ مَا نَعۡبُدُهُمۡ إِلَّا لِيُقَرِّبُونَآ إِلَى ٱللَّهِ زُلۡفَىٰٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡ فِي مَا هُمۡ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَنۡ هُوَ كَٰذِبٞ كَفَّارٞ ٣ لَّوۡ أَرَادَ ٱللَّهُ أَن يَتَّخِذَ وَلَدٗا لَّٱصۡطَفَىٰ مِمَّا يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ سُبۡحَٰنَهُۥۖ هُوَ ٱللَّهُ ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّارُ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Saukar Littafi daga Allah ne Mabuwayi, Mai hikima.

2. Lalle Mu Muka saukar maka Littafi da gaskiya, to ka bauta wa Allah kana mai tsantsanta addini a gare Shi.

3. Ku saurara! Tsantsan addini na Allah ne. Waɗanda kuwa suka riƙi wasu majiɓinta al’amari ba Shi ba (suna cewa): “Ba ma bauta musu sai kawai don su kusanta mu ga Allah.” Lalle Allah zai yi hukunci a tsakaninsu game da abin da suke sassaɓawa a cikinsa. Lalle Allah ba Ya shiryar da wanda yake maƙaryaci, mai yawan kafirci.

4. Da Allah Ya yi nufin Ya riƙi ɗa, da sai Ya zaɓi wanda Ya ga dama daga abubuwan da Yake halitta. Tsarki ya tabbata a gare Shi. Shi ne Ɗaya, Mai rinjaye.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da bayanin cewa, shi ne Allah Mabuwayi wanda babu mai iya ja da shi, mai hikima cikin ayyukansa, shi ne ya saukar da Alƙur’ani wanda gaskiya ce da babu wani kokwanto a cikinta.
Sannan ya ƙara jaddada cewa lalle shi ne ya saukar wa da Manzonsa Annabi Muhammadu (ﷺ) wannan Alƙur’ani wanda yake cike da gaskiya ta fuskar labaransa, hukunce-hukuncensa kuma duk adalci ne.
Sai kuma ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya kaɗaita shi wajen bauta tare da tsantsanta addini gare shi shi kaɗai. Ya tabbatar da cewa tsantsar addini wanda babu shirka a cikinsa nasa ne. Amma waɗanda suka riƙi wasu ababen, bauta gumaka ne ko wasunsu, suna bauta musu suna kuma fakewa da cewa, su fa ba komai ya sa suke bauta musu ba sai don kawai su kusantar da su wurin Allah, watau su isar da buƙatunsu wurinsa, su cece su a gabansa. Allah ya bayyana cewa zai yi hukunci tsakanin muminai masu kaɗaita shi da bauta da waɗannan da suke haɗa bautarsa da wasu abubuwan daban a ranar ƙiyama a kan saɓabin da suke yi game da sha’anin Tauhidi.
Allah kuma ya bayyana cewa, duk mai yi masa ƙaryar yana da abokin tarayya mai butulce wa ni’imominsa, to ba zai shiryar da shi zuwa ga tafarkin gaskiya ba, domin zai doɗe zuciyarsa, hasken shiriya ya ƙi shiga cikinta sakamakon bijire wa ayoyin Allah da ya yi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da ya yi nufin samar wa kansa ɗa, to da sai ya zaɓi abin da ya ga dama daga cikin halittarsa ya mayar da shi ɗansa. To amma Allah ya tsarkaka daga duk abin

da waɗannan mushirikan suke jingina masa na shirka, domin shi Ɗaya ne a zatinsa da siffofinsa da ayyukansa, mai rinjaye ne a kan dukkan halittunsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu, duka saboda wata babbar hikima wadda ita ce, don a bauta masa shi kaɗai ba tare da shirka ba.

2. Girman Ƙudurar Allah a cikin halittarsa wadda take nuna cancantar a bauta masa shi kaɗai.

3. Rana da wata duk suna gudu ne a magudanarsu (watau falaƙinsu), kuma suna da ƙayyadajjen lokaci da aka ɗeba musu, shi ne zuwa ƙarshen wannan rayuwar ta duniya.

4. Girman ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan'adam, tun daga kan halittarsa har zuwa abin da ya halitta masa na dabbobin da yake amfani da su a rayuwarsa.

5. Kafa hujja da Rububiyyar Allah a kan Uluhiyyarsa, watau duk wanda ya yarda da cewa Allah ne mai halitta mai ba da arziki, to ya zama dole ya amince da cewa shi kaɗai ya cancanci ya bauta wa ba wasu ba.

Suratuz Zumar (5-6)
خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّۖ يُكَوِّرُ ٱلَّيۡلَ عَلَى ٱلنَّهَارِ وَيُكَوِّرُ ٱلنَّهَارَ عَلَى ٱلَّيۡلِۖ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ كُلّٞ يَجۡرِي لِأَجَلٖ مُّسَمّٗىۗ أَلَا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡغَفَّٰرُ ٥ خَلَقَكُم مِّن نَّفۡسٖ وَٰحِدَةٖ ثُمَّ جَعَلَ مِنۡهَا زَوۡجَهَا وَأَنزَلَ لَكُم مِّنَ ٱلۡأَنۡعَٰمِ ثَمَٰنِيَةَ أَزۡوَاجٖۚ يَخۡلُقُكُمۡ فِي بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمۡ خَلۡقٗا مِّنۢ بَعۡدِ خَلۡقٖ فِي ظُلُمَٰتٖ ثَلَٰثٖۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡ لَهُ ٱلۡمُلۡكُۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ فَأَنَّىٰ تُصۡرَفُونَ ٦

5. Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya; Yana naɗa dare a kan yini, Ya kuma naɗa yini a kan dare; kuma Ya hore rana da wata; kowane yana tafiya zuwa wani lokaci ƙayyadajje. Ku saurara! Shi ne Mabuwayi, Mai yawan gafara.

6. Ya halicce ku daga rai guda (shi ne Adamu), sannan Ya halicci matarsa daga gare shi, Ya kuma halitta muku dangogi guda takwas na dabbobin ni'ima. Yana (shirya) halittarku a cikin cikkunan iyayenku mata, matakin halitta bayan wani matakin, cikin duffai guda uku. Wannan kuwa Shi ne Allah Ubangijinku; Wanda mulki nasa ne; babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi. To ta ina ne ake juyar da ku?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya halicci sammai da ƙasa ba don wasa ba, sai don wata babbar hikima da gaskiya, kuma shi ne yake sarrafa su yadda ya ga dama, yana naɗa dare a kan yini, yana kuma naɗa yini a kan dare, watau yakan sanya dare ya lulluɓe yini da duhunsa, ko ya sanya yini ya lulluɓe dare da haskensa; duk sanda ɗaya ya zo sai ɗayan ya gushe. Ya kuma hore rana da wata, kowannensu yana gudu gwargwadon lokacin da aka ƙayyade masa, watau zuwa ƙarshen rayuwar duniya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa shi ne Mabuwayi wanda zai iya saukar da uƙubarsa ga masu saɓa masa, babu mai iya hana shi, kuma mai yawan gafarar zunuban bayinsa ne waɗanda suka tuba suka nemi gafararsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jawo hankulan mutane zuwa ga hikimar halittarsu da ta dabbobinsu, da cewa ya halicce su ne daga rai ɗaya shi ne Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), daga gare shi kuma ya halicci matarsa Hauwa'u. Sannan kuma ya halitta musu dabbobin ni'ima, watau raƙuma da shanu da tumakai da awakai, nau'uka guda takwas, watau kowane nau'i jinsin namiji da mace.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, mutane da dabbobi duka ya halicce su ne a cikin cikkunan iyayensu mata, ya shirya halittarsu mataki bayan mataki a cikin duffai guda uku, duhun ciki da duhun mahaifa da kuma duhun mabiyiya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, mai yin wannan halittar shi ne Allah Ubangijinsu, kuma shi ne kaɗai mai cikakken mulki, babu wanda ya cancanta a bauta wa sai shi kaɗai, to amma abin mamaki ta yaya ake karkatar da su daga bautar mai kowa da komai zuwa bautar wanda bai halicci komai ba?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cikakken mawadacin Sarki ne, ba shi da buƙatar komai a wajen bayinsa, su ne masu buƙata a wajensa.

2. Wajabcin godiya ga Allah a kan ni'imominsa da haramcin butulce masa.

3. Ba duk abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nufa ya zamana ya yarda da shi ba. Yakan nufi bayinsa da aukawa cikin kafirci, amma bai yarda da shi ba.

4. Babu wani wanda zai iya ɗauke wa wani laifinsa, ko da kuwa shi ne ya sa shi aikata wannan laifin ya kuma yi masa alƙawarin zai ɗauke masa nauyinsa.

5. Kwaɗaitarwa a kan yin tanadi domin ranar lahira wadda zuwa gare ta kowa zai koma babu makawa.

6. Ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kewaye komai da kowa.

7. Tunawar da kafiri yake yi da Allah lokacin da ya shiga wani mawuyacin hali da saurin butulce masa yayin da ya sami sukuni, alama ce ta kiɗimewa da rashin alƙibla da yake rayuwa a cikinsa.

8. Girman karamcin Allah ga bawansa da kyautatawarsa gare shi ko da kuwa bawan kafiri ne mai saurin butulce masa.

9. Allah yakan amsa addu'ar kafiri idan ya tsantsanta addu'a a gare shi.10. Rayuwar duniya komai tsawonta taƙaitacciya ce idan an kwatanta ta da rayuwar lahira.

Suratuz Zumar (7-8)
إِن تَكۡفُرُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِيٌّ عَنكُمۡۖ وَلَا يَرۡضَىٰ لِعِبَادِهِ ٱلۡكُفۡرَۖ وَإِن تَشۡكُرُواْ يَرۡضَهُ لَكُمۡۗ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰۚ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُم مَّرۡجِعُكُمۡ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَۚ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٧ ۞وَإِذَا مَسَّ ٱلۡإِنسَٰنَ ضُرّٞ دَعَا رَبَّهُۥ مُنِيبًا إِلَيۡهِ ثُمَّ إِذَا خَوَّلَهُۥ نِعۡمَةٗ مِّنۡهُ نَسِيَ مَا كَانَ يَدۡعُوٓاْ إِلَيۡهِ مِن قَبۡلُ وَجَعَلَ لِلَّهِ أَندَادٗا لِّيُضِلَّ عَن سَبِيلِهِۦۚ قُلۡ تَمَتَّعۡ بِكُفۡرِكَ قَلِيلًاۖ إِنَّكَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلنَّارِ ٨

7. Idan kun kafirce, to lalle Allah Mawadaci ne ga barin ku, ba Ya kuma yarda da kafirci daga bayinsa. Idan kuwa kuka gode Zai yarda da godiyar taku. Kuma wani rai ba ya ɗaukar laifin wani. Sannan zuwa ga Ubangijinku ne makomarku take, sannan Ya ba ku labarin irin abubuwan da kuka kasance kuna aikatawa. Lalle Shi Masanin abubuwan da suke cikin ƙiraza ne.

8. Idan kuma wata cuta ta sami mutum sai ya roƙi Ubangijinsa yana mai komawa gare Shi, sannan idan Ya ba shi wata ni'ima daga gare Shi, sai ya manta abin da ya kasance yana roƙon Sa a da, ya kuma sanya

abokan tarayya ga Allah don ya ɓatar (da mutane) daga hanyarsa (Allah). Ka ce: “Ka ji daɗi ɗan kaɗan da kafircinka; lalle kai kam kana daga cikin ‘yan wuta.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikakkiyar wadatarsa ga ɗan’adam da cewa, ba shi ne mai amfana da ɗa’ar da ake yi masa ba, domin kuwa da mutane duk za su kafirce masa, to lalle shi mawadaci ne ba ya da buƙatar imaninsu, kafircinsu kuma ba zai cutar da shi da komai ba, sai dai su ne za su cutu da wannan kafircin.

An karɓo daga Abu Zarri (Allah ya ƙara masa yarda) daga Annabi (ﷺ) ya ce: “Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: ‘Ya ku bayina, ku ba ku isa ku cuce ni ba ballantana har ku cutar da ni, kuma ba ku isa ku amfane ni ba ballantana har ku amfanar da ni. Ya ku bayina, da a ce na farkonku da na ƙarshenku da mutanenku da aljannunku za su kasance a bisa zuciyar wanda ya fi kowa taƙawa daga cikinku, wannan ba zai ƙara komai a cikin mulkina ba. Ya ku bayina, da a ce na farkonku da na ƙarshenku da mutanenku da aljannunku za su kasance a bisa zuciyar wanda ya fi kowa fajirci daga cikinku, wannan ba zai rage komai daga mulkina ba’”. [Muslim #2577].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa ba zai taɓa yarda da kafirci daga bayinsa ba, domin bai umarce su da shi ba, saboda Allah ba ya umarni da aikata mummunan aiki. Amma idan suka gode wa ni’imominsa suka yi imani da shi, to zai yarda da godiyar tasu har ma ya yi musu kyakkyawar sakayya a kai. Watau wannan wata rahama ce daga wajensa, ba don yana da buƙatar ɗa’arsu ba kuma ba don zai cutu da kafircinsu ba, sai dai don amfanin kansu kawai.
Ya kuma tabbatar musu da cewa kowa zai ga sakamakon aikinsa ne kyakkyawa ko mummuna, domin kuwa babu wani rai da zai ɗauki laifin wani, sannan makomarsu gaba ɗayansu zuwa gare shi ne a ranar alƙiyama, zai kuma ba wa kowa labarin abin da ya aikata a duniya ya yi masa sakayya a kansa. Lalle kuma shi masanin abin da yake cikin zukatan bayinsa ne babu abin da yake ɓuya gare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata mummunar ɗabi’a ta kafiri ta butulci ga ni’imar Ubangijinsa da cewa, idan wata cuta ta sami kafiri ta rashin lafiya ko asarar dukiya ko shiga cikin halin tsoron nutsewa a ruwa da makamantansu, sai ya dage ya yi ta roƙon Allah domin ya yaye masa damuwarsa, ya koma gaba ɗaya wajen Allah shi kaɗai ba zai kira wani gunkinsa ba, to amma da zarar wata ni’ima daga Allah ta same shi, ya yaye masa cutar da ta same shi da damuwarsa, nan da nan sai ya manta da wanda ya kasance yana roƙon sa a da, watau Allah, ya ci gaba da sanya wa Allah abokan tarayya yana bauta musu don ya ɓatar da mutane daga hanyar Allah. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya faɗa wa duk mai irin wannan mummunan hali, ya ji ɗan daɗi kaɗan da kafircinsa a cikin gwargwadon abin da ya rage masa na rayuwarsa ta duniya, to amma ya sani cewa lalle shi a ranar alƙiyama yana daga cikin ‘yan wuta masu dawwama a cikinta har abada, don haka daɗin da ya ji a nan duniya bai amfana masa komai ba a wannan ranar.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kyakkyawan fata a wurin Allah da tsoron azabarsa, siffofi biyu ne na muminai.

2. Falalar masu ilimin sanin Allah a kan marasa shi.

3. Masu wa’azantuwa da ayoyin Allah su ne kawai masu lafiyayyen hankali masu fifita ilimi a kan jahilci, masu fifita ɗa’ar Allah a kan saɓonsa, domin suna da hankalin da yake sanya su kyakkyawan tunani da hangen nesa.

Suratuz Zumar (9)

أَمَّنْ هُوَ قَٰنِتٌ ءَانَآءَ ٱلَّيۡلِ سَاجِدٗا وَقَآئِمٗا يَحۡذَرُ ٱلۡأٓخِرَةَ وَيَرۡجُواْ رَحۡمَةَ رَبِّهِۦۗ قُلۡ هَلۡ يَسۡتَوِي ٱلَّذِينَ يَعۡلَمُونَ وَٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَۗ إِنَّمَا يَتَذَكَّرُ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٩

9. Shin yanzu wanda yake shi mai ibada ne a cikin sa'o'in dare, yana sujjada yana kuma tsayawa, yana tsoron ranar lahira yana kuma ƙaunar rahamar Ubangijinsa (zai yi daidai da wanda ba haka yake ba?) Ka ce: "Yanzu waɗanda suke da sani za su yi daidai da waɗanda ba su da sani? Ma'abota hankula ne kawai suke wa'azantuwa.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo wani gwaji ne tsakanin kyawawan halaye na muminai, da kuma butulcin kafirai, inda yake cewa, shin mumini mai biyayya ga Allah, mai raya lokutan darensa yana sujjada a gare shi yana tsayuwa domin bautar sa, yana kuma jin tsoron azabar lahira yana kuma fatan samun rahamar Allah, wannan ne ya fi ko kuma kafiri wanda zai bauta wa Allah idan ya shiga damuwa, amma ya kafirce masa yayin da yake cikin yalwa ya riƙa sanya masa kishiyoyi?

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya shiga wurin wani saurayi yana cikin gargarar mutuwa sai ya ce masa: "Yaya kake jin ka?" Sai ya ce: "Ya Manzon Allah, wallahi tabbas ina kyautata fata ga Allah, ina kuma tsoron zunubina." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Waɗannan abubuwa biyu ba su taɓa haɗuwa a zuciyar wani bawa a irin wannan wuri ba, face sai Allah ya ba shi abin da yake fata, ya amintar da shi daga abin da yake tsoro." [Tirmizi #983].

An karɓo daga Tanimud Dari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda ya karanta aya ɗari a cikin dare to za a rubuta masa ladan ibadar dare." [Ahmad #16958].

Sai kuma Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya faɗa wa bayinsa cewa, shin waɗanda suke da ilimin sanin Allah da haƙƙoƙinsa da shari'arsa za su zama daidai da waɗanda ba su san komai a kan haka ba? Ya tabbatar da cewa waɗanda kawai suke gane bambanci tsakanin waɗannan ɓangarori biyu su ne mutane masu lafiyayyen hankali.

Daga waɗannan ayoyin za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani da Allah da Manzonsa (ﷺ) da kyautata aiki, shi ne kaɗai zai sanya mutum ya sami kyakkyawar rayuwa a duniya da kyakkyawan sakamako a lahira na gidan Aljanna.

2. Ba ya halatta ga Musulmi ya zauna inda ba za a bar shi ya bauta wa Allah ba. Dole ne ya yi hijira zuwa inda zai sami walwalar bautar Ubangijinsa, sai dai idan abin ya fi ƙarfinsa, to sai ya yi ƙoƙarin kiyaye abin da zai iya kiyayewa na dokokin Allah gwargwadon ikonsa.

3. Wajibi ne ga mai kira zuwa ga Allah ya zama shi ne farkon wanda zai miƙa wuya ga abin da yake kiran mutane zuwa gare shi na gaskiya.

4. Manzon Allah (ﷺ) shi kansa bawan Allah ne wanda Allah ya umarce shi ya bauta masa kuma ya tsantsanta addininsa gare shi, don haka shi ma bawa ne mai cikakkiyar ɗa'a ga Allah.

5. Tsantsanta bauta ga Allah, watau ikhlasi, sharaɗi ne na karɓar kowace ibada.

6. Saɓon Allah yana jawo fushin Allah da azabarsa.

7. Girman ladan mai haƙuri a wurin Allah.

8. Wajibi ne ga mutum ya bayyana gaskiyar da yake kai kada ya damu da duk wanda ya saɓa masa a kanta, matuƙar yana da ikon yin haka.

9. Annabi (ﷺ) ya fi kowa bin umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

10. Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) yana buƙatar aikin da zai kuɓutar da shi daga azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

11. Mafi girman asarar da mutum zai yi, ita ce asarar lahira, yayin da zai yi asarar kansa da iyalansa, domin wannan ita ce asara mai ɗorewa wadda babu wata riba bayanta.

12. Tsananin azabar ‘yan wuta, domin azaba ce da za ta lulluɓe su ta samansu da kuma ƙarƙashinsu.

Suratuz Zumar (10-16)

قُلْ يَٰعِبَادِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ رَبَّكُمْۚ لِلَّذِينَ أَحْسَنُواْ فِي هَٰذِهِ ٱلدُّنْيَا حَسَنَةٌۗ وَأَرْضُ ٱللَّهِ وَٰسِعَةٌۗ إِنَّمَا يُوَفَّى ٱلصَّٰبِرُونَ أَجْرَهُم بِغَيْرِ حِسَابٖ ١٠
قُلْ إِنِّيٓ أُمِرْتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱللَّهَ مُخْلِصًا لَّهُ ٱلدِّينَ ١١ وَأُمِرْتُ لِأَنْ أَكُونَ أَوَّلَ ٱلْمُسْلِمِينَ ١٢ قُلْ إِنِّيٓ أَخَافُ إِنْ عَصَيْتُ رَبِّي عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٖ ١٣
قُلِ ٱللَّهَ أَعْبُدُ مُخْلِصًا لَّهُۥ دِينِي ١٤ فَٱعْبُدُواْ مَا شِئْتُم مِّن دُونِهِۦۗ قُلْ إِنَّ ٱلْخَٰسِرِينَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُمْ وَأَهْلِيهِمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِۗ أَلَا ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْخُسْرَانُ ٱلْمُبِينُ ١٥ لَهُم مِّن فَوْقِهِمْ ظُلَلٞ مِّنَ ٱلنَّارِ وَمِن تَحْتِهِمْ ظُلَلٞۚ ذَٰلِكَ يُخَوِّفُ ٱللَّهُ بِهِۦ عِبَادَهُۥۚ يَٰعِبَادِ فَٱتَّقُونِ ١٦

10. Ka ce: “Ya ku bayina waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Ubangijinku. Waɗanda suka kyautata a wannan duniyar suna da kyakkyawan (sakamako). Kasar Allah kuma yalwatacciya ce. Lalle masu haƙuri ne kawai ake cika wa ladansu ba da lissafi ba.”

11. Ka ce: “Lalle ni an umarce ni da in bauta wa Allah ina mai tsantsanta addini gare Shi.

12. “An kuma umarce ni da in kasance farkon Musulmi.”

13. Ka ce: “Lalle ni ina jin tsoron azabar wani yini mai girma idan na saɓi Ubangijina”

14. Ka ce: “Allah kawai nake bauta wa, ina mai tsantsanta addinina gare Shi.

15. “Sai ku bauta wa abin da kuka ga dama ba Shi ba.” Ka ce: “Lalle asararru (su ne) waɗanda suka yi asarar rayuwarsu da ta iyalinsu ranar alƙiyama. Ku saurara! Wannan ita ce asara bayyananniya.

16. Suna da inuwoyi na wuta a samansu, a ƙarƙashinsu kuma akwai wasu inuwoyin. Wannan ne fa Allah Yake tsoratar da bayinsa da shi. Ya ku bayina, sai ku kiyaye dokokina.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya yi wa bayinsa muminai umarni kan su ji tsoron Ubangijinsu su kiyaye dokokinsa, ya kuma sanar da su cewa duk wanda ya kyautata aikinsa to yana da kyakkyawan sakamako a nan duniya, na samun taimako da ƙoshin lafiya da wadatar arziki, a lahira kuma yana da sakamakon gidan Aljanna.

Sai kuma ya kwaɗaitar da su da yin hijira daga inda aka hana su bautar Allah zuwa inda za su sami sararin bauta masa, su kuma yi haƙuri da zafin raɗaɗin barin gidajensu; lalle ƙasar Allah tana da yalwa, don haka kada su takura wa kawunansu. Ya tabbatar musu da cewa masu haƙuri a kan bin Allah da guje wa saɓonsa da jure wa ƙaddararsa marar daɗi su ne kawai za a cika musu ladansu ranar alƙiyama ba tare da lissafi ba saboda yawansa.
Sannan ya umarci Annabi (ﷺ) da cewa ya sanar da mushirikai cewa shi fa an umarce shi ne ya bauta wa Allah shi kaɗai ya kuma tsantsanta addininsa gare shi, don haka kada su yi tsammanin zai yarda ya bauta wa wani abu da suke bauta wa, kuma an umarce shi ya zamanto farkon wanda ya miƙa wuya ga Allah a cikin wannan al'umma. Kuma ya shaida musu cewa shi kansa yana jin tsoron idan har ya saɓa wa Ubangijinsa bai yi masa biyayya yadda ya kamata ba, to yana tsoron azabar wani yini mai girma, watau ranar alƙiyama.
Allah kuma ya sake umartar sa da ya tabbatar musu da cewa shi fa Allah kaɗai yake bauta wa, yana tsarkake addininsa gare shi shi kaɗai, don haka su su je su bauta wa duk abin da suka ga dama, su ne za su gamu da mummunan ƙarshe, kuma za su tafka mummunar asara a ranar alƙiyama idan ba su tuba ba, lalle kuwa asararru na gaske su ne waɗanda suka yi asarar kawunansu da iyalansu a ranar alƙiyama, kuma wannan ita ce asara mabayyaniya. Watau ko dai iyalansu sun bi Allah a nan duniya sun shiga Aljanna a lahira, su kuma sun ɓata a duniya an jefa su wuta a lahira, don haka sun yi rabuwa ta har abada; ko kuma dukkansu sun mutu a kan kafirci, sun shiga wuta, kowa yana ta kansa babu wanda ya damu da wani. To lalle wannan ita ce babbar asara ta gaske.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin da za su tsinci kansu a cikin wuta a ranar alƙiyama da cewa, suna da wasu inuwowi na hayaƙi da harshen wuta da tsananin zafi a samansu da ƙarƙashinsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shaida musu cewa, da irin wannan azabar ce yake tsoratar da bayinsa, don haka ya umarce su da lallai su kiyaye dokokinsa su aikata abin da ya umarce su kuma su guje wa abin da ya hana su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa muminai kyakkyawan albishir tun a rayuwarsu ta duniya na samun kyakkyawan yabo daga mutane da kuma kyakkyawan mafarki da kulawa daga Ubangiji. Sannan suna da wani albishir a lahira wanda za su fara samu tun daga lokacin mutuwa da cikin ƙabari da kuma lokacin da alƙiyama ta tsaya. Mafi girman albishirinsu shi ne na samun shiga Aljanna da dacewa da yardar Allah da ganin fuskarsa mai girma.

2. Daga cikin kyawawan siffofin muminai akwai sauraron magana da ɗaukar wadda ta fi kyau. Mafi kyan magana kuwa ita ce maganar Allah da ta Manzonsa (ﷺ). Suna fifita maganar Allah da ta Manzo (ﷺ) a kan maganar kowa, ba sa kaucewa su bi maganar wani.

3. Yana daga cikin alamar masu hankali su iya tantance maganganu da ɗaukar mafi kyau su bar munana. Amma wanda ba ya iya tantance kyakkyawar magana daga mummuna, to wannan ba ya daga cikin mutane masu lafiyayyen hankali. Hakanan wanda zai iya tantancewa amma son zuciya ya fi ƙarfinsa, sai ya watsar da mai kyau ya kama abin da ya fi dacewa da sha'awarsa da son ransa.

4. Duk wanda yake da kwaɗayin sauraron magana don ya kama wadda ta fi kyau ta fi alheri, to wannan shi ne wanda Allah ya so shi da shiriya. Amma wanda ya ji ba ya son sauraron gaskiya ko kyakkyawar magana to ya tuhumi kansa, domin ba ya daga cikin waɗanda aka nufa da shiriya.

5. Duk wanda azabar Allah ta riga ta tabbata a kansa, to babu mai iya shiryar da shi.

6. Annabi (ﷺ) ba zai iya tsamo kafirin da aka jefa wuta ba ballantana waninsa.

7. Gidajen Aljanna benaye ne wasu saman wasu.

Suratuz Zumar (17-20)
وَٱلَّذِينَ ٱجۡتَنَبُواْ ٱلطَّٰغُوتَ أَن يَعۡبُدُوهَا وَأَنَابُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ لَهُمُ ٱلۡبُشۡرَىٰۚ فَبَشِّرۡ عِبَادِ ١٧ ٱلَّذِينَ يَسۡتَمِعُونَ ٱلۡقَوۡلَ فَيَتَّبِعُونَ أَحۡسَنَهُۥٓۚ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ هَدَىٰهُمُ ٱللَّهُۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ١٨ أَفَمَنۡ حَقَّ عَلَيۡهِ كَلِمَةُ ٱلۡعَذَابِ أَفَأَنتَ تُنقِذُ مَن فِي ٱلنَّارِ ١٩ لَٰكِنِ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ رَبَّهُمۡ لَهُمۡ غُرَفٞ مِّن فَوۡقِهَا غُرَفٞ مَّبۡنِيَّةٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَعۡدَ ٱللَّهِ لَا يُخۡلِفُ ٱللَّهُ ٱلۡمِيعَادَ ٢٠

17. Waɗanda kuwa suka nisanci bautar ɗagutu, suka kuma koma ga Allah, suna da albishir (na Aljanna). To ka yi wa bayina aibishir.

18. Waɗanda suke sauraron magana sai su bi mafi kyawunta, waɗannan su ne waɗanda Allah Ya shiriya, kuma waɗannan su ne ma’abota hankula.

19. Yanzu wanda kalmar azaba ta tabbata a kansa (kai ne za ka iya shiyar da shi)? Yanzu kai za ka iya kuɓutar da wanda yake cikin wuta?

20. Sai dai waɗanda suka kiyaye dokokin Ubangijinsu suna da ɗakunan benaye, a sama da su kuma akwai wasu ɗakunan benaye ginannu, ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu; (wannan) alƙawarin Allah ne; Allah ko ba Ya saɓa alƙawari.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu siffofin bayinsa nagari da kyakkyawan sakamako da ya yi musu alƙawari, da cewa su ne waɗanda suka nisanci bautar gumaka da duk wani abin bauta ba Allah ba, suka kuma tuba zuwa ga Allah; to waɗannan suna da albishir na Aljanna a lokacin mutuwarsu da lokacin da suke cikin ƙaburburansu da kuma ranar alƙiyama. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya yi wa bayinsa nagari albishir da ni’imomin gidan Aljanna. Ya kuma siffanta su da cewa su ne waɗanda suke sauraron magana sai su tantance tsakanin mai kyau da mummuna, sai su bi mafi kyan magana mafi amfani. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa masu siffofi irin waɗannan, su ne waɗanda ya yi wa dacen shiriya, kuma masu lafiyayyen hankali waɗanda suka san abin da ya dace da su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shaida wa Manzonsa cewa duk wanda azabarsa ta tabbata a kansa saboda dogewarsa a kan kafirci da ɓata, to Manzo (ﷺ) ya sani ba ya da wata dabara ta shiryar da shi har ya karɓi gaskiya, don haka ba zai iya ceto shi daga shiga wuta ba bayan ya siffantu da siffar kafirci ya mutu a kanta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka siffantu da siffar taƙawa; suka yi aiki da umarnin Allah suka guji haninsa, da cewa suna da manyan gidajen bene wasu kan wasu waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Wannan kuma alƙawari ne Allah ya yi musu, shi kuma ba ya saɓa alƙawari idan ya yi.

An karɓo daga Aliyyu ɗan Abu Ɗalib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle a gidan Aljanna akwai wasu benaye waɗanda ake ganin bayansu daga cikinsu, ake kuma ganin cikinsu daga bayansu.” Sai wani mutumin ƙauye ya tashi ya ce: “Na wane ne su ya Manzon Allah?” Sai ya ce: “Na wanda ya kyautata maganarsa ne, ya kuma ciyar da abinci, ya dimanci yin azumi, ya kuma yi salla da daddare yayin da mutane suke barci.” [Tirmizi #1984 da Ahmad #1338].

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle ‘yan Aljanna suna hango mutanen benaye a samansu kamar yadda kuke hango tauraro mai haske mai tafiya a sasannin sama daga gabas ko daga yamma, saboda fifikon da yake tsakaninsu.” Sai sahabbai suka ce: “Ya Manzon Allah, waɗannan ai gidaje ne na annabawa; babu mai samun su sai su kaɗai.” Sai ya ce: “E, haka ne. Na rantse da wanda raina yake hannunsa, akwai kuma wasu mazaje waɗanda suka yi imani da Allah suka kuma gaskata manzanni.” – watau su ma za su sami waɗannan gidajen – [Bukhari #3257 da Muslim #2831].

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Asalin ruwan da ke ƙasa, daga sama Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake saukar da shi.

2. Wata babbar hikimar Allah da rahamarsa da ke cikin saukar da ruwa daga sama shi ne, don ya iya game ko'ina da ina; tudu da kwari ya sauka har kan duwatsu. Da a ce ta ƙasa kawai ruwa yake ɓuɓbugowa, to da ba zai kai ga wasu tuddai da duwatsu ba har sai ya shanye mutane da gidajensu da dukiyoyinsa.

3. Masu hankali su ne masu wa’azantuwa da ɗaukar izina daga kulawar da Allah yake yi wa bayinsa da rahamarsa gare su, ta yadda ya sauƙaƙe musu ruwa ya ajiye musu shi a cikin ƙasa domin amfaninsu. Wannan yana ƙara nuna musu cikar Kudurar Allah da yalwar rahamarsa.

4. Kamar yadda Allah yake raya ƙasa bayan mutuwarta, to hakanan zai raya matattu ya tashe su don yi musu hisabi.

5. Ishara zuwa ga saurin gushewar duniya da ƙyale-ƙyalenta, kamar yadda shuka koriya mai ban sha’awa take saurin zama busasshiya rududdugagga.

Suratuz Zumar (21)
أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَسَلَكَهُۥ يَنَٰبِيعَ فِي ٱلۡأَرۡضِ ثُمَّ يُخۡرِجُ بِهِۦ زَرۡعٗا مُّخۡتَلِفًا أَلۡوَٰنُهُۥ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَىٰهُ مُصۡفَرّٗا ثُمَّ يَجۡعَلُهُۥ حُطَٰمًاۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَذِكۡرَىٰ لِأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ٢١

21. Yanzu ba ka gani cewa Allah ne Ya saukar da ruwa daga sama, sannan Ya shigar da shi cikin idanuwan ruwa a ƙasa, sannan Yana fitar da shukoki masu launi iri-iri da shi, sannan ya bushe sai ka gan shi fatsi-fatsi, sannan Ya mayar da shi dudduga? Lalle a game da wannan tabbas akwai wa’azi ga ma’abota hankula.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin Manzonsa (ﷺ) game da saurin gushewar duniya da abin da yake cikinta na jin daɗi da cewa, ya duba ya ga yadda ya saukar da ruwa daga sama, sannan ya shigar da shi cikin idanuwan ruwa da magudanansa a ƙasa, sannan da wannan ruwa ya fitar da shukoki masu launi iri-iri. Sai daga baya wannan shukar ta bushe ta yi fatsi-fatsi bayan a da tana koriya shar; sannan bayan ta bushe sai Allah ya mayar da ita dudduga. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa lalle a cikin wannan aiki nasa akwai wa’azantarwa ga masu hankula lafiyayyu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shiriya ta Allah ce don haka a wajensa kaɗai ake neman ta. Kuma kada mutum ya riƙa jiji da kai don ya ga ya shiriya; kamata ya yi ya yi wa Allah godiya da ya zaɓe shi ya shiryar da shi.

2. Duk wanda ya yi imani da Allah da Manzonsa (ﷺ), ya kuma rungumi addinin Musulunci, to wannan yana tare da wani haske daga Allah, watau hasken imani da shiriya da sakankancewa da alƙawarin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Duk wanda ya bar ambaton Allah, to zuciyarsa za ta ƙeƙashe, sannan kuma ya cancanci wani mummunan sakamako daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Zukata iri biyu ne: Akwai zukatan da suke laushi su yi sanyi da ambaton Allah; akwai kuma waɗanda suke ƙeƙashewa saboda watsi da ambaton Allah da suka yi.

5. Duk wanda ya bar ambaton Allah har zuciyarsa ta ƙeƙashe, to lalle ya tsunduma cikin ɓata bayyananne.

6. Tabbatar da cewa Alƙur'ani shi ne mafi kyan zance domin maganar Allah ne, don haka ya tabbata cewa kalmominsa da lafuzzansa su suka fi kowaɗanne kalmomi da lafuzza fasaha da azanci, kuma ma'anoninsa sun fi kowaɗanne ma'anoni daraja da martaba.

7. Alƙur'ani ya fi kowanne irin littafi fasaha da azancin magana, domin komai a cikinsa bibbiyu ne.

8. Masu imani da tsoron Allah su ne masu ƙasƙantar da kansu da nutsuwa yayin da suke sauraron karatun Alƙur'ani.

Suratuz Zumar (22-28)

أَفَمَن شَرَحَ ٱللَّهُ صَدۡرَهُۥ لِلۡإِسۡلَٰمِ فَهُوَ عَلَىٰ نُورٖ مِّن رَّبِّهِۦۚ فَوَيۡلٞ لِّلۡقَٰسِيَةِ قُلُوبُهُم مِّن ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ٢٢ ٱللَّهُ نَزَّلَ أَحۡسَنَ ٱلۡحَدِيثِ كِتَٰبٗا مُّتَشَٰبِهٗا مَّثَانِيَ تَقۡشَعِرُّ مِنۡهُ جُلُودُ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُمۡ ثُمَّ تَلِينُ جُلُودُهُمۡ وَقُلُوبُهُمۡ إِلَىٰ ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ هُدَى ٱللَّهِ يَهۡدِي بِهِۦ مَن يَشَآءُۚ وَمَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنۡ هَادٍ ٢٣ أَفَمَن يَتَّقِي بِوَجۡهِهِۦ سُوٓءَ ٱلۡعَذَابِ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ وَقِيلَ لِلظَّٰلِمِينَ ذُوقُواْ مَا كُنتُمۡ تَكۡسِبُونَ ٢٤ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ فَأَتَىٰهُمُ ٱلۡعَذَابُ مِنۡ حَيۡثُ لَا يَشۡعُرُونَ ٢٥ فَأَذَاقَهُمُ ٱللَّهُ ٱلۡخِزۡيَ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَعَذَابُ ٱلۡأٓخِرَةِ أَكۡبَرُۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٢٦ وَلَقَدۡ ضَرَبۡنَا لِلنَّاسِ فِي هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٖ لَّعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ٢٧ قُرۡءَانًا عَرَبِيًّا غَيۡرَ ذِي عِوَجٖ لَّعَلَّهُمۡ يَتَّقُونَ ٢٨

22. Yanzu wanda Allah Ya buɗa masa ƙirjinsa da Musulunci don haka ya zama cikin haske daga Ubangijinsa (zai yi kamar wanda zuciyarsa ta ƙeƙashe?) To tsananin azaba ya tabbata ga masu ƙeƙasassun zukata da ba sa ambaton Allah. Waɗannan suna cikin ɓata mabayyani.

23. Allah Ya saukar da mafi kyan zance: Alƙur'ani mai kama da juna, mai biyunta (saƙo), tsikar fatun waɗanda suke tsoron Ubangijinsu suna tashi, sannan fatunsu su yi taushi, zukatansu kuwa su koma zuwa ambaton Allah. Wannan ita ce shiriyar Allah, Yana shiyar da wanda Ya ga dama da ita. Wanda kuma Allah Ya ɓatar to ba shi da mai shiryar da shi.

24. Yanzu wanda yake kare mummunar azaba da fuskarsa a ranar alƙiyama (zai yi kama da wanda ba ya yi?) Aka kuma ce da azzalumai: "Ku ɗanɗani abin da kuka kasance kuna aikatawa."

25. Waɗanda suke gabaninsu sun ƙaryata, sai azaba ta zo musu daga inda ba sa tsammani.

26. Sannan Allah Ya ɗanɗana musu azabar wulaƙanci a rayuwar duniya, kuma lalle azabar lahira ta fi girma. Da sun kasance sun san (hakan).

27. Kuma haƙiƙa Mun ba wa mutane kowane nau'i na misali a cikin wannan Alƙur’ani don su wa’azantu.

28. Alƙur’ani Balarabe marar karkata don su sami taƙawa.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi cikakken bayani na wajabcin komawa ga bautarsa da guje wa ruɗin duniya, sai kuma bayyana cewa babu mai amfana da wannan bayani nasa sai wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yalwata masa ƙirjinsa ya buɗe masa zuciyarsa ya haskaka masa ita da hasken imani. Allah kuma ya yi tambaya cewa, shin yanzu mutumin da Allah ya yi masa irin wannan buɗin ya shiriya ya kama addinin Musulunci yana gudanar da rayuwarsa a kan basira da haske daga Ubangijinsa, zai zama ɗaya da wanda zuciyarsa ta riga ta ƙeƙashe babu ambaton Allah tare da shi? Lalle amsa ita ce ba za su zama ɗaya ba har abada, domin shiryayye shi ne zai samu kuɓuta a wurin Allah, wanda kuwa zuciyarsa ta ƙeƙashe shi ya yi hasara ta har abada. Kuma masu ƙeƙasassun zukata suna cikin ɓata bayyananne.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwarzanta littafinsa Alƙur’ani da cewa shi ne littafi mafi kyan zance da ya saukar wa Annabi Muhammadu (ﷺ) wanda kuma yake da kamanceceniya da juna a wajen gaskiya da kyan tsari da azancin Magana; sashinsa kuma ba ya warware wani sashi. Yana kuma biyunta batutuwansa da saƙwanninsa; ya ƙunshi ƙissoshi mabambanta da hukunce-hukunce iri-iri, da gargaɗi da albishir, da bayanin siffofin masu gaskiya da siffofin maƙaryata da sauran batutuwa daban-daban. Idan masu tsoron Ubangijinsu suka saurari abin da yake cikinsa na gargaɗi da tsoratarwa sai duk tsakar jikinsu ta riƙa tashi, sannan idan suka saurari abin da ya ƙunsa na albishir da kyakkyawan fata sai fatarsu ta yi laushi hankalinsu ya kwanta, su koma zuwa ga ambaton Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Sai kuma ya bayyana cewa wannan tasirin na Alƙur’ani da aka ambata shiriya ce daga Allah da yake shiryar da wanda ya ga dama da ita, amma kuma duk wanda ya ɓatar ya hana masa shiriya to babu wanda ya isa ya shiryar da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo bambanci tsakanin shiryayyen mutum da taɓaɓɓe, da cewa ba za su taɓa zama ɗaya ba. Watau ba za a daidaita wanda Allah ya shiryar da shi, ya ba shi ikon yin aikin shiga Aljanna ya kuma shigar da shi cikinta a lahira, da mutumin da ya kafirce wa Allah ya mutu a kan kafirci, aka jefa shi cikin wuta yana a ƙuƙumce ba. Lalle wannan ya tabbata cikin azzalumai waɗanda a ranar za a ce da su su ɗanɗani mummunan sakamakon abin da suka riƙa aikatawa a duniya na kafirci da saɓon Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa al’ummun da suka gabaci waɗannan mushirikai su ma sun ƙaryata manzannin da ya aika musu, sai azaba ta zo musu kwatsam ta inda ba sa tsammani ballantana su yi shirin tuba zuwa ga Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗanɗana musu azabar wulaƙanci da tozarta tun a nan duniya, kuma lalle azabar lahira da take jiran su ta fi wannan girma da tsanani, da a ce sun san haka.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa a duk labaran da yake ba su a cikin littafinsa Alƙur’ani na mutanen kirki da na banza da bayanin gaskiya da ƙarya, to yana yin haka ne domin mutane su wa’azantu su saki ƙarya su kama gaskiya. Ya kuma tabbatar musu da cewa ya saukar da Alƙur’ani da harshen Larabci babu kuma wata karkata a cikinsa ko wani abu mai wahalar fahimta, don su karanta shi su kiyaye dokokin Allah da yake yi musu bayani a cikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur’ani littafi ne da Allah ya bayyana komai a cikinsa dalla-dalla tare da misalai.

2. Duk mai haɗa Allah da wani a bauta ba zai taɓa samun natsuwar zuciya ba ko kwanciyar hankali. Mumini mai kaɗaita Allah ne kaɗai yake samun natsuwa da kwanciyar hankali domin abin bautarsa ɗaya shi ne Allah.

3. Tabbatar da cewa duk wani mahaluƙi zai mutu ya koma ga Allah.

4. Allah shi kaɗai ne ya cancanci kamalar yabo da cikar godiya domin shi kaɗai ne ba shi da abokin tarayya.

5. Yawancin ‘yan’adam sun jahilci haƙiƙanin yadda matsayin Allah yake, don haka suke yin shirka da shi.

6. Dukkan halittu sai sun yi husuma a gaban Allah ranar alƙiyama, domin a bayyana mai gaskiya da marar gaskiya da mai imani da kafiri, kuma a mayar wa da kowa haƙƙinsa.

Suratuz Zumar (29-31)
ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا رَّجُلًا فِيهِ شُرَكَآءُ مُتَشَٰكِسُونَ وَرَجُلًا سَلَمًا لِّرَجُلٍ هَلۡ يَسۡتَوِيَانِ مَثَلًاۚ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِۚ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٢٩ إِنَّكَ مَيِّتٞ وَإِنَّهُم مَّيِّتُونَ ٣٠ ثُمَّ إِنَّكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ عِندَ رَبِّكُمۡ تَخۡتَصِمُونَ ٣١

29. Allah Ya ba da misali na wani namiji (bawa) wanda yake da iyayen giji masu tarayya a kansa masu jayayya (a kan ba shi umarni) da kuma wani namiiji (bawa) da ya keɓanta ga wani namiji guda, shin misalinsu za su yi daidai? Dukkan yabo ya tabbata ga Allah. A’a, yawancinsu dai ba su sani ba ne.

30. Lalle kai mai mutuwa ne, su ma kuma lalle masu mutuwa ne.

31. Sannan kuma lalle ku ɗin nan a ranar alƙiyama a wurin Ubangijinku za ku yi husuma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar da misalin mutumin da yake shirka da mutumin da yake kaɗaita Allah, ya haɗa misalinsu da wani bawa da iyayen giji suka yi tarayayya a kansa, sannan suna ba shi umarni daban-daban, idan ya daɗaɗa wa wani daga cikinsu sai ya fusata wani, don haka yana cikin ɗimuwa da rashin sanin abin yi don ya gamsar da kowa daga cikin iyayen gijinsa. Sai kuma ga wani bawa wanda ya keɓanta ga mutum guda shi ne ubangijinsa, ya san me yake so mene ne ba ya so, don haka yana gudanar da ayyukansa tare da shi cikin kwanciyar hankali da nutsuwa. To shin waɗannan mutane biyu za su zama ɗaya wajen kwanciyar hankali da nutsuwa? Lalle ba za su zama daidai ba. Sai Allah ya yabi kansa ya kuma tabbatar da cewa yawancin masu shirka da shi ba su san haka ba, shi ya sa suke haɗa shi da wasu wajen bautarsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, babu makawa kowa sai ya mutu ya koma gare shi, babu mai dawwama a bayan ƙasa, har da shi kansa Manzo (ﷺ) shi ma mai barin duniya ne, don haka dukkansu za su haɗu a gaban Allah ranar alƙiyama inda za a raba musu gardamar abin da suke husuma a kansa, a bayyana mai gaskiya da maƙaryaci.

An karɓo daga Zubairu ɗan Awwam (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Yayin da wannan ayar ta sauka sai na ce: Ya Manzon Allah, yanzu sai an sake dawo mana abin da ya kasance a tsakaninmu (na husuma) tare da laifukan da muka yi a keɓe? Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “E, sai an dawo muku da su, har sai an mayar wa da kowa haƙƙinsa.” Sai Zubairu ya ce: “Lalle al’amarin mai tsanani ne.” [Tirmizi #3356 da Ahmad #1434].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mafi girman zalunci shi ne mutum ya yi wa Allah ƙarya, ya kuma ƙaryata gaskiyar da ta zo masa daga wurin Allah.

2. Wajabcin yin taka-tsantsan wajen fassara maganar Allah, domin duk wanda ya yi gangancin fassara maganarsa ba tare da ilimi ba, to yana cikin haɗarin yi wa Allah ƙarya.

3. Makomar ƙarshe ga kafirai ba ita ce mutuwa ba, makomarsu ita ce wutar Jahannama. Kamar yadda muminai makomarsu ta ƙarshe ita ce Aljanna.

4. Gaskiya tana daga cikin taƙawa, don haka gaskata mai ita ma taƙawa ce.

5. Taƙawa tana daga cikin ihsani, watau kyautayi.

Suratuz Zumar (32-35)

*فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن كَذَبَ عَلَى ٱللَّهِ وَكَذَّبَ بِٱلصِّدْقِ إِذْ جَآءَهُۥٓ ۚ أَلَيْسَ فِى جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْكَٰفِرِينَ ﴿٣٢﴾ وَٱلَّذِى جَآءَ بِٱلصِّدْقِ وَصَدَّقَ بِهِۦٓ ۙ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ ﴿٣٣﴾ لَهُم مَّا يَشَآءُونَ عِندَ رَبِّهِمْ ۚ ذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلْمُحْسِنِينَ ﴿٣٤﴾ لِيُكَفِّرَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ أَسْوَأَ ٱلَّذِى عَمِلُوا۟ وَيَجْزِيَهُمْ أَجْرَهُم بِأَحْسَنِ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿٣٥﴾

32. Wane ne ya fi zalunci fiye da wanda ya yi wa Allah ƙarya, ya kuma ƙaryata gaskiya lokacin da ta zo masa? Yanzu a cikin wutar Jahannama babu wurin zaman kafirai?

33. Wanda kuwa ya zo da gaskiya ya kuma gaskata ta, waɗannan su ne masu taƙawa.

34. Suna da (sakamakon) abin da suke so daga wurin Ubangijinsu. Wannan shi ne sakamakon masu kyautatawa.

35. Don Allah Ya kankare musu mafi munin abin da suka aikata, Ya kuma saka musu ladansu da mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu azzalumin da ya fi wanda ya dangana wa Allah abokin tarayya, ko ya ce yana da ɗa ko mata don kawai ya ƙira wa Allah ƙaryar abin da bai dace ba. Hakanan babu azzalumin da ya fi wanda ya ƙaryata wahayin da aka yi wa Manzon Allah na Alƙur'ani. Idan mutum ya haɗa yi wa Allah ƙarya da kuma ƙaryata manzannin Allah to babu shakka wannan girman zaluncinsa ya wuce iyaka. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa a cikin Jahannama akwai mazauni ga duk wani kafiri azzalumi da ya butulce wa Ubangijinsa.
To bayan Allah ya ambaci mai ƙarya kuma mai ƙaryata gaskiya, sai kuma ya ambaci sakamakon wanda ya zo da gaskiya cikin maganganunsa da ayyukansa kamar annabawa da mabiyansu, ya kuma gaskata wannan gaskiyar ya yi imani da ita ya yi aiki da ita. Allah ya tabbatar da cewa waɗannan su ne masu taƙawa na gaskiya, domin su ne suke aiki da umarninsa suke guje wa haninsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa suna da sakamakon duk abin da suka ga dama suka so a wurin Ubangijinsu na ni'imomi na har abada. Allah ya bayyana cewa wannan shi ne sakamakon masu kyautata ayyukansu tsakaninsu da Ubangijinsu da kuma bayinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi musu wannan sakamako ne, domin ya kankare musu mafi munin laifukan da suka aikata a duniya suka tuba zuwa ga Allah, ya kuma saka musu da sakamako mafi kyau daga ayyukan da suka aikata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa cewa, zai ba shi kariya daga abokan gabarsa.

2. Tabbatar da Tauhidi na Rububiyya kaɗai ba tare da tabbatar da na Uluhiyya ba wannan ba zai amfanar da bawa ba a wurin Allah.

3. Duk wanda ya tsaya a kan bautar Allah shi kaɗai ya tsantsanta dogaronsa da shi, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ishe shi komai a duniya da lahira, babu mai iya cutar da shi da abin da Allah bai rubuta masa ba, ko ya amfanar da shi da abin da bai ƙaddara masa ba.

4. Shiriya da ɓata duka suna hannun Allah ne, don haka a wurinsa kaɗai ake roƙon shiriya ba wurin wani ba.

5. Bijire wa kiran Manzo (ﷺ) ba zai sa shi ya daina abin da Allah ya umarce shi da shi ba na kiran mutane zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, domin kuwa kowa a ƙarshe zai gane sakamakon aikinsa mai kyau ko mummuna.

Suratuz Zumar (36-40)
أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِكَافٍ عَبْدَهُۥ ۖ وَيُخَوِّفُونَكَ بِٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦ ۚ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنْ هَادٍ ﴿٣٦﴾ وَمَن يَهْدِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن مُّضِلٍّ ۗ أَلَيْسَ ٱللَّهُ
بِعَزِيزٍ ذِى ٱنتِقَامٍ ﴿٣٧﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۚ قُلْ أَفَرَءَيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ إِنْ أَرَادَنِىَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ هَلْ
هُنَّ كَٰشِفَٰتُ ضُرِّهِۦٓ أَوْ أَرَادَنِى بِرَحْمَةٍ هَلْ هُنَّ مُمْسِكَٰتُ رَحْمَتِهِۦ ۚ قُلْ حَسْبِىَ ٱللَّهُ ۖ عَلَيْهِ يَتَوَكَّلُ ٱلْمُتَوَكِّلُونَ ﴿٣٨﴾ قُلْ يَٰقَوْمِ ٱعْمَلُوا۟ عَلَىٰ مَكَانَتِكُمْ
إِنِّى عَٰمِلٌ ۖ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ﴿٣٩﴾ مَن يَأْتِيهِ عَذَابٌ يُخْزِيهِ وَيَحِلُّ عَلَيْهِ عَذَابٌ مُّقِيمٌ ﴿٤٠﴾

36. Yanzu Allah bai ishi bawansa ba? Suna kuma tsorata ka da waɗanda suke ba Shi ba. Wanda kuwa Allah Ya ɓatar to babu wani mai shiryar da shi.

37. Wanda kuma Allah Ya shiryar da shi to babu wani mai ɓatar da shi. Yanzu Allah ba Mabuwayi ba ne, Mai ramuwar gayya?

38. Tabbas da za ka tambaye su wanda ya halicci sammai da ƙasa, lalle za su ce: “Allah ne.” Ka ce (da su): “Ku ba ni labarin waɗanda kuke bauta wa ba Allah ba, idan Allah Ya nufe ni da wata cuta, yanzu za su iya yaye cutar tasa, ko kuwa idan Ya nufe ni da rahama yanzu za su iya riƙe rahamarsa?” Ka ce: “Allah Ya ishe ni; a gare Shi ne kawai masu dogaro suke dogaro.”

39. Ka ce: “Ya ku mutanena, ku yi aiki a kan irin hanyarku, ni ma kuma zan yi aiki ne (a kan irin tawa), sannu ba da daɗewa ba za ku sani.

40. “Wanda azabar da za ta kunyata shi za ta zo masa, kuma azaba madawwamiya za ta sauka a kansa.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, zai kula da bawansa Annabi Muhammadu (ﷺ) wanda ya tsaya kyam a kan bautarsa da cika umarninsa, zai biya masa buƙatunsa na duniya da na lahira, don haka ya ishe shi komai a rayuwarsa don babu wanda zai iya cutar da shi. Su kuma mushirikai saboda toshewar basirarsu da ɓatan da suke ciki wai har suna tsoratar da shi gumakansu da suke bauta wa suna cewa za su iya cutar da shi. Ba shakka wannan ɓatansu ne da toshewar basira; duk kuwa wanda Allah ya riga ya ɓatar to babu mai iya shiryar da shi, wanda kuma ya shiryar to babu mai ɓatar da shi. Sai kuma Allah ya nuna musu cewa, shi Mabuwayin Sarki ne da babu mai iya rinjayar sa, kuma mai yin uƙuba ga duk wanda ya kafirce masa kuma ya mutu bai tuba ba.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa, mushirikai sun san Allah shi ne mahaliccin komai, Rububiyya tasa ce shi kaɗai. Kuma da zai tambaye su cewa wane ne ya halicci sammai da ƙasa, da za su tabbatar masa da cewa Allah ne ya halicce su. Don haka ya umarce shi da ya nuna musu kasawar gumakansu da suke bauta wa ba Allah ba, kuma ya tambaye su cewa idan har Allah ya nufe shi da wata cuta, shin gumakan za su iya yaye masa wannan cutar? Ko kuma idan ya yi nufin sa da wata rahama gumakansu za su iya hana wannan rahamar ta same shi? Don haka ya tabbatar musu da cewa Allah kaɗai ne abin bauta, kuma shi kaɗai ne ma'ishinsa, kuma a gare shi shi kaɗai ya dogara, kuma lallai duk masu dogara su dogara gare shi, shi kaɗai ne zai iya biya musu buƙatunsu, ya share musu hawayensu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya yi wa mushirikai kashedi game da abin da suke dagewa a kansa na shirka, da cewa su ci gaba da aikata shirkarsu ta bautar gumaka, shi ma zai ci gaba da aikin da Allah ya umarce shi da shi na kira zuwa ga Tauhidi da tsantsanta bauta ga Allah shi kaɗai, ba da jimawa ba za su san wane ne zai samu kyakkyawan ƙarshe; za kuma su gane wanda azaba za ta riƙe shi tun a nan duniya ta wulaƙanta shi, sannan kuma a lahira ya gamu da wata mummunar azaba madawwamiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk abin da Alƙur'ani ya ƙunsa na labarai da hukunce-hukunce gaskiya ne, don haka duk abin da ya ci karo da shi ƙarya ne.

2. Allah cikakken mawadaci ne, ba shi da buƙatar komai a wurin kowa, ba ya amfana don wani ya shiriya, ba kuma ya cutuwa saboda ɓatan wani.

3. Annabi Muhammadu (ﷺ) ba mai tsaro ne a kan kowa ba, shi Manzo ne da Allah ya umarce shi da ya isar da saƙo kawai.

4. Karfin Kudurar Allah da ikonsa wajen tasarrufi da rayukan halittarsa yadda ya ga dama.

Suratuz Zumar (41-45)
إِنَّآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ لِلنَّاسِ بِٱلۡحَقِّۖ فَمَنِ ٱهۡتَدَىٰ فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيۡهَاۖ وَمَآ أَنتَ عَلَيۡهِم بِوَكِيلٍ ٤١ ٱللَّهُ يَتَوَفَّى ٱلۡأَنفُسَ
حِينَ مَوۡتِهَا وَٱلَّتِي لَمۡ تَمُتۡ فِي مَنَامِهَاۖ فَيُمۡسِكُ ٱلَّتِي قَضَىٰ عَلَيۡهَا ٱلۡمَوۡتَ وَيُرۡسِلُ ٱلۡأُخۡرَىٰٓ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمًّىۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ
يَتَفَكَّرُونَ ٤٢ أَمِ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ شُفَعَآءَۚ قُلۡ أَوَلَوۡ كَانُواْ لَا يَمۡلِكُونَ شَيۡـٔٗا وَلَا يَعۡقِلُونَ ٤٣ قُل لِّلَّهِ ٱلشَّفَٰعَةُ جَمِيعٗاۖ لَّهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِۖ ثُمَّ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٤٤ وَإِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَحۡدَهُ ٱشۡمَأَزَّتۡ قُلُوبُ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِۖ وَإِذَا ذُكِرَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦٓ إِذَا هُمۡ يَسۡتَبۡشِرُونَ ٤٥

41. Lalle Mu Mun saukar maka da Littafi da gaskiya ga mutane; saboda haka duk wanda ya shiriya to ya yi wa kansa alheri, wanda kuwa ya ɓata, to lalle ya ɓata ne don kansa; kuma kai ba wakili ba ne a kansu.

42. Allah Yana karɓar rayuka lokacin mutuwarsu, da waɗanda kuma ba su mutu ba a lokacin baccinsu; sai Ya riƙe waɗanda Ya ƙaddara wa mutuwa, Ya kuma saki sauran har zuwa wani lokaci ƙayyadadde. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu tunani.

43. Tabbas sun dai riƙi wasu masu ceto ne ba Allah ba. Ka ce: "Yanzu (kwa yi haka) ko da kuwa sun kasance ba sa mallakin komai, kuma ba sa hankalta?"

44. Ka ce: “Ceto gaba ɗaya na Allah ne; mulkin sammai da ƙasa nasa ne Shi kaɗai; sannan kuma wurinsa ne kawai za a komar da ku.”

45. Idan kuma aka ambaci Allah Shi kaɗai sai zukatan waɗanda ba sa ba da gaskiya da ranar lahira su takura; idan kuwa aka ambaci waɗanda suke ba Shi ba sai ka gan su suna ta walwala.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi zuciyar Manzonsa (ﷺ) ya kwantar masa da hankali game da abin da yake fuskanta na tirjiyar mutanensa da kafewarsu a kan kafirci da cewa, ya saukar masa da Alƙur’ani ne da gaskiya don ya gargaɗi mutane da shi ya tsayar musu da hujjar Allah a kansu, don haka duk wanda ya shiriya to ya shiriya ne don kansa domin shi ne zai amfana da shiriyarsa ba Allah ba; duk kuma wanda ya ɓata to babu shakka kansa kawai zai cutar; ɓatansa ba zai cutar da Allah da komai ba. Ya kuma nuna wa Manzonsa cewa shi fa ba an aiko shi ne don ya tursasa wani kan ya yi imani ba; shi kawai aikin da aka ɗora masa shi ne isar da saƙon Allah gare su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wani nau’i na Kudurarsa da ikonsa na gudanar da rayuwar ɗan’adam, da cewa, shi ne yake karɓar rayuka lokacin mutuwarsu yayin da ajalinsu ya cika, yake kuma karɓar rayukan waɗanda lokacin mutuwarsu bai zo ba yayin barcinsu. Sai ya riƙe ruhin wanda ya ƙaddara wa mutuwa a wurinsa, ya kuma saki wanda bai ƙaddara mutuwarsa a lokacin ba har zuwa wani ƙayyadajjen lokaci da ya bar wa kansa saninsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa a cikin waɗannan ayyuka nasa akwai ayoyi ga mutane masu tunani su gane cewa lalle wanda duk yake iya wannan aiki to zai iya tayar da mutane bayan mutuwa domin yi musu hisabi.

An karɓo daga Abu Hurairah (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Idan ɗayanku ya je wajen kwanciyarsa to ya kakkaɓe shi da cikin mayafinsa, domin bai san abin da ya maye gurbinsa ba a bayansa, sannan ya ce: “Da sunanka ya Ubangijina na kwantar da ɓarin jikina, da kuma taimakonka ne zan ɗaga shi; idan ka riƙe raina to ka gafarta masa, idan kuma ka sako shi to ka tsare shi da abin da kake tsare bayinka salihai da shi.” [Bukhari #6320 da Muslim #2714].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mushirikai sun ɗauki gumaka suna bauta musu domin tsammanin wai za su cece su a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) za kuma su amfane su a rayuwarsu ta duniya. Sai ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya tambaye su cewa shin za su riƙa bautar gumaka ne ko da kuwa ba za su mallaka wa kansu wani amfani ba ballantana har su mallaka musu wani abu? Kuma ko da ba sa hankaltar komai, sun kasance daskararrun abubuwa waɗanda ba sa ji ba sa gani ba sa kuma iya magana, sannan ba sa cutarwa ko amfanarwa?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya faɗa musu cewa lalle ceto gaba ɗaya na Allah ne, kuma babu mai ceto sai da izininsa, babu kuma wanda za a ceta sai wanda Allah ya yarda a cece shi. Kuma su sani cewa mulkin sammai da ƙasa duk nasa ne shi kaɗai, kuma zuwa gare shi kaɗai za a mayar da su ranar alƙiyama domin yi musu hisabi a kan ayyukansu.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani mummunan hali na mushirikai wanda yake nuna cewa sam ba su san girman Allah ba, watau duk sanda aka ambaci Allah shi kaɗai sai zukatan mushirikai waɗanda ba su yi imani da ranar lahira ba su yi matuƙar takura, su ji ba sa son jin wannan maganar. Amma idan aka ambaci gumakan da suke bauta wa ba Allah ba sai ka gan su suna ta farin ciki da walwala.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne ga bawa ya yawaita komawa ga Allah yana roƙon sa shiriya cikin dukkan al’amuransa, kada ya riƙa ruɗuwa da iliminsa ko fahimtarsa.

2. Mafi girman saɓani tsakanin mutane shi ne wanda yake tsakanin muminai masu kaɗaita Allah da bauta, masu miƙa wuya ga umarninsa, masu hanuwa da haninsa, da kuma mushirikai masu bautar wasu ba Allah ba, masu bijire wa umarnin Allah da yawan saɓon Allah da bijire wa shari'arsa ɗungurungum. Daga shi sai saɓanin da ke tsakanin masu tsantsanta biyayya ga shiriyar littafin Allah da sunnar Manzonsa da kauce wa duk wani abu da ya ci karo da su, da kuma waɗanda suke fifita wasu hanyoyi a kan hanyar Manzon Allah, suna girmama maganganun wasu fiye da maganganun Manzo (ﷺ) da rashin bin dokokin shari'a sau da ƙafa. Sai kuma saɓanin da ke tsakanin Musulmi masu ɗa'a ga Allah da Manzonsa da jin tsoron sa a ɓoye da sarari, da kuma masu saɓon Allah da bin son zuciya da sha'awe-sha'awe na duniya. Bawa yana buƙatar roƙon Allah shiriyarsa da tallafawarsa cikin waɗannan al'amura gaba ɗaya.

3. Duk tsananin rowar kafiri a duniya zai yi burin a lahira ya fanshi kansa da duk wani abu mai daraja da ya mallaka a duniya daga azabar Allah, da za a yarda a karɓa daga gare shi.

Suratuz Zumar (46-48)

قُلِ ٱللَّهُمَّ فَاطِرَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ عَٰلِمَ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ أَنتَ تَحۡكُمُ بَيۡنَ عِبَادِكَ فِي مَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ﴿٤٦﴾ وَلَوۡ أَنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ مَا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا وَمِثۡلَهُۥ مَعَهُۥ لَٱفۡتَدَوۡاْ بِهِۦ مِن سُوٓءِ ٱلۡعَذَابِ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ وَبَدَا لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مَا لَمۡ يَكُونُواْ يَحۡتَسِبُونَ ﴿٤٧﴾ وَبَدَا لَهُمۡ سَيِّـَٔاتُ مَا كَسَبُواْ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ﴿٤٨﴾

46. Ka ce: "Ya Allah Mahaliccin sammai da ƙasa, Masanin ɓoye da sarari, Kai ne za Ka yi hukunci tsakanin bayinka game da abin da suka kasance suna yin saɓani a kansa."

47. Da a ce waɗanda suka yi zalunci za su mallaki abin da yake bayan ƙasa baki ɗaya har da wani kamarsa a tare da shi, to da sun fanshi kansu da shi saboda munin azabar ranar lahira. Abin da kuma ba su kasance suna tsammani daga Allah ba ya bayyana a gare su.

48. Kuma munanan abubuwan da suka aikata suka bayyana a gare su, abin kuma da suka kasance suna yi wa izgili ya auka musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya roƙi Ubangijinsa shiriya, ya mayar da duk al'amuransa gare shi, ya roƙe shi da sunansa Allah mahaliccin sammai da ƙasa ba tare da ya kwaikwaya a wurin wani ba, masanin abin da yake ɓoye da wanda yake sarari, ya kuma tabbatar da cewa shi ne kaɗai zai yi hukunci a tsakanin bayinsa ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna saɓani a kansa a duniya, ya bayyana mai gaskiya da marar gaskiya a tsakaninsu.

An karɓo daga Abu Salama ya ce: Na tambayi A'isha, (Allah ya kara mata yarda) na ce: "Da me Manzon Allah (ﷺ) ya kasance yana buɗe sallarsa idan ya tashi cikin dare?" Sai ta ce: "Ya kasance idan ya tashi cikin dare yakan buɗe sallarsa da cewa: "Ya Allah Ubangijin Jibrila da Mika'ila da Israfila, wanda ya ƙagi halittar sammai da ƙasa, masanin abin da yake ɓoye da na sarari, kai ne kake yin hukunci a tsakanin bayinka game da abin da suka kasance suna saɓani a cikinsu, ka nuna mini gaskiya a cikin abin da suke saɓani a kansa da izininka, lalle kai ne kake shiryar da wanda ka ga dama zuwa ga tafarki madaidaici." [Muslim #770].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan sakamako na waɗanda suka zalunci kawunansu a duniya ta hanyar shirka da saɓon Allah, da cewa da za su mallaki duk wata dukiya da duk wani abu mai tsada a bayan ƙasa, to da sun fanshi kawunansu da shi daga matsananciyar azabar da za su fuskanta a ranar alƙiyama. Kuma abin da ba su taɓa tsammanin ganin sa na azabar Allah ba ya bayyana a

gare su; sai kuma ga shi mummunan sakamakon abin da suka aikata na shirka da saɓon Allah ya bayyana a gare su, sannan kuma azabar da suke yi wa izgili a duniya sai ga shi ta baibaye su ta ko'ina.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin butulcin kafiri ga mahaliccinsa.

2. Duk ni'imar da Allah zai ba wa kafiri a nan duniya talala ce yake yi masa.

3. Hatsarin ji-ji da kai da muninsa, domin ɗabi'a ce ta kafirai.

4. Allah yakan jarrabi bawa da ni'ima kamar yadda yake jarrabar sa da musiba.

5. Yawancin mutane ba sa gane cewa Allah yakan jarrabi wanda ya ga dama da ni'imomin rayuwa ne, sai su zaci wannan wani dalili ne da yake nuna Allah ya yarda da bawa, sai su ci gaba da aikata abin da suke kai na saɓon Allah, wai a zatonsu da yana fushi da su to da bai ba su wannan ni'imar ba.

6. Duk yawan dukiyar da mutum zai tara a duniya da manyan matsayi da zai taka ba zai amfana masa komai a wurin Allah ba, sai ya je da kyawawan ayyuka.

7. Samun arziki da rashinsa duk nufin Allah ne, don haka lallai mutum ya nemi komai a wurin Allah kuma ya dogara da shi shi kaɗai.

Suratuz Zumar (49-52)
فَإِذَا مَسَّ ٱلۡإِنسَٰنَ ضُرّٞ دَعَانَا ثُمَّ إِذَا خَوَّلۡنَٰهُ نِعۡمَةٗ مِّنَّا قَالَ إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلۡمِۭۚ بَلۡ هِيَ فِتۡنَةٞ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٤٩ قَدۡ قَالَهَا ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ فَمَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٥٠ فَأَصَابَهُمۡ سَيِّـَٔاتُ مَا كَسَبُواْۚ وَٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنۡ هَٰٓؤُلَآءِ سَيُصِيبُهُمۡ سَيِّـَٔاتُ مَا كَسَبُواْ وَمَا هُم بِمُعۡجِزِينَ ٥١ أَوَ لَمۡ يَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقۡدِرُۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٥٢

49. To idan wata cuta ta samu mutum sai ya roƙe Mu, sannan idan Mun ba shi wata ni'ima daga gare Mu sai ya ce: "Ai an ba ni ita ne kawai don sanin (cancantata)". Ba haka ba ne, ita wata jarrabawa ce kawai, sai dai yawancinsu ba sa sanin (haka).

50. Haƙiƙa waɗanda suke gabaninsu sun faɗe ita (wannan maganar), to abin da suka kasance suna aikatawa bai wadatar da su (komai) ba.

51. Saboda haka sai (sakamakon) mummunan abin da suka aikata ya same su. Waɗanda ma suka yi zalunci daga waɗannan, (sakamakon) munanan abubuwan da suka aikata zai same su, kuma ba za su gagara ba.

52. Yanzu ba su sani ba ne cewa, Allah Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, Yana kuma ƙuntata wa (ga wanda ya ga dama)? Lalle a game da waɗannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu yin imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata mummunar ɗabi'a ta kafirai wadda take nuna tsananin butulcinsu da rashin godiyarsu gare shi da cewa, idan wata damuwa ta samu wani kafiri ta rashin lafiya ko talauci da makamantansu, to sai ya roƙi Allah don ya yaye masa ita. To amma idan Allah ya biya masa buƙatarsa, ya ba shi lafiya ko dukiya sai ya riƙa cewa, ai Allah ya ba shi wannan ne don ya cancanci

ya ba shi, bai san cewa Allah yana yi masa talala ne yana jarrabar sa da wannan ba. To amma yawancin kafirai ba su san haka ba, shi ya sa suke ruɗuwa da ni'imar da aka ba su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa irin wannan mummunar maganar da take fita daga bakin wannan kafiri, kafiran baya ma sun sha faɗar irinta, sun kuma yi ta ruɗuwa da yawan dukiyoyinsu da matsayin da suke a kai, to amma abin da suka riƙa aikatawa bai tsinana musu komai ba.
Allah ya tabbatar da cewa mummunan sakamakon abin da suka aikata na shirka da saɓon Allah ya same su. Su ma kuma waɗanda suka zalunci kansu da aikata shirka da saɓon Allah cikin al'ummar Annabi Muhammadu (ﷺ), irin sakamakon da zai same su kenan, kuma ba za su gagari Allah ba ko su kuɓuce masa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi masu irin waccan ɗanyar magana cewa shin ba su san Allah shi ne yake yalwata wa wanda ya ga dama arziki ba don ya jarraba shi ya ga ko zai gode masa ko kuma zai butulce? Shi ne kuma yake ƙuntata arziki ga wanda ya ga dama don shi ma ya jarraba shi ya ga ko zai yi haƙuri ko zai nuna fushinsa ga ƙaddarar Allah? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa a cikin irin wannan aiki nasa akwai ayoyi masu nuna yadda Allah yake tsara al'amuransa ya gudanar da su a kan wannan tsarin ga mutane masu imani, domin su ne suke amfana da irin waɗannan ayoyi, amma kafirai suna ganin ba sa amfana da komai daga cikinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yalwar rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa. Duk irin laifin da bawa zai yi idan ya tuba zuwa ga Allah ya bar wannan laifin, to Allah zai gafarta masa ya karɓi tubansa.

2. Haramcin ɗebe ƙauna daga rahamar Allah, domin babu mai ɗebe ƙauna daga rahamarsa sai kafiri.

3. Wajabcin komawa ga Allah cikin dukkan al'amuran bawa da miƙa wuya zuwa gare shi, yin haka yana nuna ikhlasin bawa, wanda idan mutum ya rasa shi, to duk ayyukansa ba za su karɓu ba a wurin Allah.

4. Wajabcin aiki da Alƙur'ani domin shi ne mafi kyan abin da aka saukar cikin littattafan Allah.

5. An ambaci abubuwa da rai zai riƙa saƙawa a ranar alƙiyama a jere daki-daki, inda zai fara da nadama game da abin da ya jefa kansa a ciki, sannan ya fara nemo wa kansa uzuri don tsammanin ko zai sami kuɓuta, sannan sai ya shiga burin ina ma za a mayar da shi duniya don ya kyautata aikinsa.

Suratuz Zumar (53-59)
*قُلۡ يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ أَسۡرَفُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ لَا تَقۡنَطُواْ مِن رَّحۡمَةِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًاۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٥٣ وَأَنِيبُوٓاْ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ وَأَسۡلِمُواْ لَهُۥ مِن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَكُمُ ٱلۡعَذَابُ ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ ٥٤ وَٱتَّبِعُوٓاْ أَحۡسَنَ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكُم مِّن رَّبِّكُم مِّن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَكُمُ ٱلۡعَذَابُ بَغۡتَةٗ وَأَنتُمۡ لَا تَشۡعُرُونَ ٥٥ أَن تَقُولَ نَفۡسٞ يَٰحَسۡرَتَىٰ عَلَىٰ مَا فَرَّطتُ فِي جَنۢبِ ٱللَّهِ وَإِن كُنتُ لَمِنَ ٱلسَّٰخِرِينَ ٥٦ أَوۡ تَقُولَ لَوۡ أَنَّ ٱللَّهَ هَدَىٰنِي لَكُنتُ مِنَ ٱلۡمُتَّقِينَ ٥٧ أَوۡ تَقُولَ حِينَ تَرَى ٱلۡعَذَابَ لَوۡ أَنَّ لِي كَرَّةٗ فَأَكُونَ مِنَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٥٨ بَلَىٰ قَدۡ جَآءَتۡكَ ءَايَٰتِي فَكَذَّبۡتَ بِهَا وَٱسۡتَكۡبَرۡتَ وَكُنتَ مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٥٩

53. Ka ce: "Ya ku bayina waɗanda suka ɓata kawunansu sosai (da kafirci da saɓon Allah), kada ku ɗebe ƙauna daga rahamar Allah. Lalle Allah Yana gafarta zunubai baki ɗaya. Lalle Shi Mai gafara ne, Mai rahama.

54. "Ku kuma koma zuwa ga Ubangijinku, ku kuma miƙa wuya gare Shi tun gabanin azaba ta zo muku sannan ba za a taimake ku ba.

55. “Kuma ku bi mafi kyan abin da aka saukar muku daga Ubangijinku tun gabanin azaba ta zo muku ba zato ba tsammani, alhali ku ba ku sani ba.

56. “Don kada wani rai ya ce: ‘Kaicona game da abin da na yi sakaci na haƙƙin Allah, ni tabbas na kasance daga masu yin izgili.’

57. “Ko kuma ya ce: ‘Da Allah Ya shirye ni da tabbas na kasance daga masu taƙawa.’58. “Ko kuma ya ce lokacin da ya ga azaba: ‘Ina ma da ina da damar komawa duniya, don in kasance daga masu kyautatawa?’”

59. (Sai a ce da shi): “A’a, haƙiƙa ayoyina sun zo maka sai ka ƙaryata su ka kuma yi girman kai ka kasance daga kafirai.”

A waɗannan ayoyi, bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi kafirai sai kuma ya zo da bayanin rahamarsa da falalarsa ga muminai, ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya kirawo bayinsa waɗanda suka zaƙe da yawa wajen saɓon Allah har ma da shirka da cewa, kada su ɗebe ƙaunar samun rahamar Allah da gafarar zunubansu, domin Allah yana gafarta zunubai baki ɗaya ga duk wanda ya tuba, domin shi mai rahama ne ga bayinsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Waɗannan ayoyin sun sauka ne game da al’amarin Ayyash ɗan Abu Rabi’ah da Al-Walid ɗan Walid da wasu Musulmi. Sun musulunta, amma sai aka fitine su aka dinga azabtar da su har suka sake komawa ga shirka. Sai muka riƙa cewa: ‘Har abada Allah ba zai karɓi nafilarsu da farillarsu ba; mutane su musulunta sannan don an azabtar da su sai su bar addininsu?’ Sai waɗannan ayoyin suka sauka. Umar ɗan Khaɗɗab ya kasance marubuci ne sai ya rubuta su da hannunsa ya aika su zuwa ga Ayyash da Walid da waɗannan jama’ar da suka musulunta, sai suka musulunta suka kuma yiwo hijira.” [Ibn Jarir, *Jami’ul Bayan*, Juzu’i na 20, shafi na 227-228].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wasu mutane masu shirka sun kashe mutane da yawa, sun yi zinace-zinace da dama, sai suka zo wurin Annabi (ﷺ) suka ce: “Lalle abin da kake faɗa kuma kake kira zuwa gare shi abu ne mai kyau, to ina ma za ka tabbatar mana cewa akwai kaffara ga abubuwan da muka aikata.” Sai faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta sauka: “Su ne waɗanda ba sa bauta wa wani abin bauta tare da Allah, ba sa kuma kashe ran da Allah ya haramta ba da haƙƙi ba, ba sa zina....” [Al-Furƙan, aya ta 67]; wannan aya ita ma ta sauka. [Bukhari #4810 da Muslim #122].

An karɓo daga Amru ɗan Abasa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani tsoho ya zo wurin Annabi (ﷺ) yana dogarawa da sandarsa ya ce: “Ya Manzon Allah, na karya alƙawura, na yi rashin mutunci da yawa, shin za a gafarta mini kuwa?” Sai Manzon Allah ya ce: “Shin ba kana shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah ba?” Ya ce: “Kwarai na yi, ina kuma shaidawa lalle kai Manzon Allah ne.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Haƙiƙa an gafarta maka karya alƙawuran da ka yi da rashin mutunci da ka yi.” [Ahmad #19432].

Sai Allah ya umarci bayinsa da su koma zuwa gare shi ta hanyar tuba da kyawawan ayyuka, kuma su miƙa wuya gare shi, tun kafin azaba ta zo musu a ranar alƙiyama, sannan ba za su sami wasu masu taimakon su ba daga gumakansu ko iyalansu su kuɓutar da su daga wannan azabar.
Sannan kuma ya umarce su da su bi Alƙur’ani wanda shi ne mafi kyan abin da Ubangijinsu ya saukar wa Manzonsa (ﷺ), su bi umarninsa su kuma guji haninsa kafin azaba ta zo musu ba zato ba tsammani, ba kuma tare da sun san da zuwanta ba ballantana su yi mata kyakkyawan tanadi su tuba zuwa ga Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa ya yi musu wannan umarni ne don kada wani mai rai ya zo yana nadama ranar alƙiyama, yana cizon ɗan yatsa a kan babban sakaci da ya yi game da sha’anin Allah, ya rayu a kan kafirci da saɓon Allah da yi wa muminai izgili saboda sun yi imani sun bi Allah.

Ko kuma wani mai rai ya zo ranar alƙiyama yana kafa hujja da ƙaddara, yana cewa da Allah ya shirye shi da ya kasance daga cikin masu taƙawa, masu bin umarninsa da guje wa haninsa.
Ko kuma bayan ya ga azaba ƙarara ya riƙa burin ina ma za a mayar da shi duniya ya tuba ya zama cikin masu kyautata ayyukansu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wani ɗan wuta zai ga mazauninsa a Aljanna sai ya ce: 'Ina ma a ce Allah ya shirye ni.' Sai ya zame masa nadama. Duk wani ɗan Aljanna zai ga mazauninsa a wuta sai ya ce: 'Yanzu ba don Allah ya shirye ni ba.' watau da ya hallaka. Sai ya zamo masa godiya ga Allah. [Ahmad #10652].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa masa cewa, abin ba kamar yadda yake iƙirari ba ne, domin kuwa lalle ayoyin Allah sun zo masa amma sai ya ƙaryata su ya yi girman kai, ya kasance daga cikin masu kafirce wa Allah da ayoyinsa da manzanninsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman kai mummunar ɗabi'a ce da take hana mutum ya karɓi gaskiya.

2. Baƙar fuska a ranar alƙiyama alama ce ta taɓewa da rashin rabo.

3. Taƙawa ita ce dalilin samun kubutar bawa a ranar alƙiyama daga azabar Allah.

Suratuz Zumar (60-61)
وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ تَرَى ٱلَّذِينَ كَذَبُواْ عَلَى ٱللَّهِ وُجُوهُهُم مُّسۡوَدَّةٌۚ أَلَيۡسَ فِي جَهَنَّمَ مَثۡوٗى لِّلۡمُتَكَبِّرِينَ ٦٠ وَيُنَجِّي ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ بِمَفَازَتِهِمۡ لَا يَمَسُّهُمُ ٱلسُّوٓءُ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٦١

60. A ranar alƙiyama kuwa za ka ga waɗanda suka yi wa Allah ƙarya fuskokinsu baƙi ƙirin. Yanzu a cikin wutar Jahannama ashe babu mazaunar masu girman kai?

61. Allah kuma zai tserar da waɗanda suka yi taƙawa da ayyukansu, wani mummunan abu ba zai shafe su ba, kuma ba za su yi baƙin ciki ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, a ranar alƙiyama zai ga waɗanda suke yi wa Allah ƙarya a nan duniya, suka danganta masa abokin tarayya ko suka ce yana da ɗa, fuskokinsu sun yi baƙi ƙirin na alamar suna cikin matsananciyar wahala da taɓewa, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ya yi wa waɗannan mutane masu girman kai tanadin mazauni a cikin Jahannama saboda girman kansu da ya hana su yin imani da Allah da manzanninsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci sakamakon muminai masu taƙawa, da cewa zai tserar da su daga azaba, ya shigar da su wurin samun babban rabo shi ne Aljanna, babu kuma wata azaba da za ta shafe su, ba kuma za su yi baƙin cikin abin da suka baro a duniya ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani abu ba Allah ba to halittacce ne, kuma Allah ne mahaliccinsa.

2. Kowa da komai yana cikin kulawar Allah, don haka shi kaɗai ne abin dogaro, kuma a wurinsa ake neman taimako.

3. Taskokin alherai duka suna wurin Allah, don haka idan ya buɗe wa mutane ƙofofin rahamarsa babu mai iya rufe su, idan kuma ya rufe su babu wanda ya isa ya buɗe su sai shi.

4. Kafirci babbar asara ce a duniya da lahira wadda babu asarar da ta kai ta girma.

5. Girman haɗarin shirka da muninta. Duka annabawa an sanar da su cewa shirka tana lalata dukkan ayyuka na ƙwarai.

6. Kamar yadda bawa yake yi wa Allah godiya a kan ni'imomin duniya, hakanan ya zamanto wajibi ya yi masa godiya a kan ni'imar addini, musamman ni'imar bautar Allah shi kaɗai, watau Tauhidi.

7. Tabbatar wa Allah siffar damƙa da kuma hannun dama ba tare da kamanceceniya da na halittarsa ba.

Suratuz Zumar (62-67)

ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ وَكِيلٞ ٦٢ لَّهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٦٣ قُلۡ أَفَغَيۡرَ ٱللَّهِ تَأۡمُرُوٓنِّيٓ أَعۡبُدُ أَيُّهَا ٱلۡجَٰهِلُونَ ٦٤ وَلَقَدۡ أُوحِيَ إِلَيۡكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكَ لَئِنۡ أَشۡرَكۡتَ لَيَحۡبَطَنَّ عَمَلُكَ وَلَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٦٥ بَلِ ٱللَّهَ فَٱعۡبُدۡ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ٦٦ وَمَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ قَدۡرِهِۦ وَٱلۡأَرۡضُ جَمِيعٗا قَبۡضَتُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ مَطۡوِيَّٰتُۢ بِيَمِينِهِۦۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٦٧

62. Allah ne Mahaliccin komai; kuma Shi ne Wakili a kan komai.

63. Mabuɗan sammai da ƙasa nasa ne. Waɗanda kuwa suka kafirce wa ayoyin Allah, waɗannan su ne asararru.

64. Ka ce: "Yanzu wanin Allah kuke umarta ta da in bauta wa, ya ku waɗannan wawaye?"

65. Haƙiƙa kuma an yi maka wahayi kai da waɗanda suka gabace ka cewa: "Tabbas idan ka yi shirka lallai aikinka zai ɓaci, kuma tabbas za ka kasance daga asararru."

66. A'a, Allah kaɗai za ka bauta wa, ka kuma kasance daga masu godiya.

67. Ba su kuma girmama Allah ba kamar yadda Ya cancanta a girmama Shi, alhali ƙasa ga baki ɗayanta tana cikin Damƙarsa ranar alƙiyama, sammai kuma suna nannaɗe a Hannunsa na dama. Tsarki ya tabbata a gare Shi, Ya kuma ɗaukaka game da abin da suke yin shirka (da shi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi ne mahaliccin komai shi kaɗai, kuma shi ne wakili mai kula da kowa da komai, shi ne yake gudanar da kowane abu yadda ya so. Kuma mabuɗan taskokin alheri da ke cikin sammai da na ƙasa duka nasa ne shi kaɗai; yana yin kyauta ga wanda ya ga dama, ya kuma hana wanda ya ga dama. Ya kuma tabbatar wa kafirai cewa su ne suka yi hasara saboda sun kafirce wa ayoyinsa sun ƙi yin imani a rayuwarsu ta duniya, don haka a lahira duka wuta za su shiga kuma su dawwama a cikinta har abada.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya sanar da mushirikai waɗanda suke ta kiran sa a kan ya dawo ya bauta wa gumakansu, ya watsar da addinin kaɗaita Allah da bauta cewa, yanzu su jahilai marasa tunani da hankali su ne za su riƙa kiran sa ya zo ya bauta wa gumakansu, duk da cewa ya san babu wanda ya cancanci a bauta masa sai Allah shi kaɗai? To su sani cewa wannan abu ba zai taɓa yiwuwa ba har abada.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) kashedi, (amma yana nufin al'ummarsa) cewa lalle ya yi masa wahayi, ya kuma yi wa manzannin da suka gabace shi wahayi cewa tabbas idan ya kuskura ya yi shirka, watau ya bauta wa wani tare da Allah, to babu shakka ladan aikinsa na ƙwarai gaba ɗaya zai ɓaci, kuma tabbas zai kasance daga cikin hasararru waɗanda suka yi hasarar duniya da lahira.
Allah ya nuna masa cewa, ba shi da wani zaɓi face ya bauta wa Allah shi kaɗai, kada ya kuskura ya haɗa shi da wani, ya kuma zamanto cikin masu godiya a gare shi bisa ni'imomin da ya yi masa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mushirikai ba su girmama Allah yadda ya cancanta su girmama shi ba, yayin da suka yi tarayya da shi, suka haɗa shi da wasu gajiyayyu daga cikin halittarsa, suka manta da girman Kudurarsa wadda daga cikinta ƙasa da abubuwan da suke bayanta na duwatsu da bishiyoyi da koguna da ƙoramu a ranar alƙiyama dukansu suna cikin damƙarsa ne, sammai bakwai kuwa gaba ɗayansu suna nannaɗe ne a hannun damansa. Ya kuma ɗaukaka daga duk abin da mushirikai suke tara shi da su.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani malamin Yahudawa ya zo wurin Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya Muhammadu, mu mun samu (a littattafanmu) cewa Allah zai sanya sammai a kan ɗan yatsansa, ya sanya ƙassai a kan ɗan yatsa, ya sanya bishiyoyi a kan ɗan yatsa, ya sanya ruwa da turɓaya a kan ɗan yatsa, ya sanya sauran halittu a kan ɗan yatsa, sai ya ce: 'Ni ne mai mulki.' Sai Manzon Allah (ﷺ) ya fashe da dariya har sai da fiƙoƙinsa suka fito don gaskata maganar Bayahuden malamin nan, sannan ya karanta wannan ayar." [Bukhari #4811 da Muslim #2786].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Allah zai damƙi ƙasa, ya naɗe sama da hannunsa na dama, sannan ya ce: 'Ni ne Sarki, ina sarakunan duniya suke?'" [Bukhari #4812].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da busar ƙaho sau biyu kafin tsayuwar alƙiyama.

2. Tabbatar da siffar Allah ta haske.

3. Tabbatar da adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratuz Zumar (68-70)
وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَصَعِقَ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا مَن شَآءَ ٱللَّهُۖ ثُمَّ نُفِخَ فِيهِ أُخۡرَىٰ فَإِذَا هُمۡ قِيَامٞ يَنظُرُونَ ٦٨ وَأَشۡرَقَتِ ٱلۡأَرۡضُ بِنُورِ رَبِّهَا وَوُضِعَ ٱلۡكِتَٰبُ وَجِاْيٓءَ بِٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَقُضِيَ بَيۡنَهُم بِٱلۡحَقِّ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ٦٩ وَوُفِّيَتۡ كُلُّ نَفۡسٖ مَّا عَمِلَتۡ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِمَا يَفۡعَلُونَ ٧٠

68. Aka kuma busa ƙaho, sai duk abin da yake cikin sammai da ƙasa ya halaka sai wanda Allah Ya ga dama; sannan aka sake yin wata busar, sai ga su a tsaye suna jiran tsammani.

69. Kasa kuma ta yi haske da hasken Ubangijinta, aka kuma ajiye takardu (na ayyuka), kuma aka zo da annabawa da masu shaida, kuma aka yi hukunci a tsakaninsu da gaskiya, ba kuma za a zalunce su ba.

70. Aka kuma yi wa kowane rai cikakken sakamakon abin da ya aikata, Shi ko (Allah) Yana sane da abin da suke aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ranar da mala'ika mai riƙe da ƙaho zai busa ƙaho, a lokacin duk halittun da suke cikin sammai da na ƙasa za su mutu, sannan ya sake yin wata busar ta biyu sai ga su tsaitsaye suna sauraron yadda Allah zai yi da su.
Sannan idan Ubangiji (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zo domin yi wa bayi hisabi, sai ƙasa ta yi haske da haskensa, sai kuma a baje takardun ayyukan mutane, sai a zo da annabawa, a kuma zo da al'ummar Annabi Muhammadu (ﷺ) don su ba da shaida game da cewa annabawa duka sun isar wa al'ummunsu saƙon Allah. Sai Allah ya yi musu hukunci na adalci gaba ɗayansu, babu wanda za a zalunta a ranar, ba za a ƙara masa laifin da bai aikata ba, ba kuma za a rage masa ladansa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kowane rai za a ba shi sakamakon aikinsa cikakke, na alheri ne ko na sharri, domin kuma Allah shi ne masanin abin da suke aikatawa mai kyau ko mummuna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mummunan wulaƙancin da kafirai za su gamu da shi a ranar alƙiyama.

2. Kafirai za su shiga wutar Jahannama ƙungiya-ƙungiya, kowace ƙungiya gwargwadon girman kafircinta.

3. Tabbatar da cewa wutar Jahannama tana da ƙofofi.

4. Tabbatar da cewa wutar Jahannama tana da masu tsaron ta.

5. Babu wata al'umma da za a sanya a wuta sai bayan hujjar Allah ta zo musu sun kafirce mata.

6. Kafirai masu dawwama ne a cikin wutar Jahannama.

Suratuz Zumar (71-72)
وَسِيقَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِلَىٰ جَهَنَّمَ زُمَرًاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا فُتِحَتۡ أَبۡوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمۡ خَزَنَتُهَآ أَلَمۡ يَأۡتِكُمۡ رُسُلٞ مِّنكُمۡ يَتۡلُونَ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتِ رَبِّكُمۡ وَيُنذِرُونَكُمۡ لِقَآءَ يَوۡمِكُمۡ هَٰذَاۚ قَالُواْ بَلَىٰ وَلَٰكِنۡ حَقَّتۡ كَلِمَةُ ٱلۡعَذَابِ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧١ قِيلَ ٱدۡخُلُوٓاْ أَبۡوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ فَبِئۡسَ مَثۡوَى ٱلۡمُتَكَبِّرِينَ ٧٢

71. Aka kuma ingiza ƙeyar waɗanda suka kafirta zuwa (wutar) Jahannama ƙungiya-ƙungiya; har yayin da suka zo wurinta sai aka buɗe ƙofofinta, masu tsaronta suka ce (da su): "Yanzu manzanni daga cikinku ba su zo muku ba ne suna karanta muku ayoyin Ubangijinku, suna kuma gargaɗin ku game haɗuwa da wannan ranar taku?" Sai suka ce: "Haka ne, (sun zo mana)," sai dai kuma kalmar azaba ta tabbata a kan kafirai."

72. Aka ce: "Ku shiga ƙofofin Jahannama, kuna masu dawwama a cikinta;" to makomar masu girman kai ta munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon kafirai bayan an gama yi musu hisabi, inda mala'iku za su gargaɗa su zuwa Jahannama a wulaƙance ƙungiya-ƙungiya, har sai sun iso ƙofar

Jahannama sai mala’iku masu tsaron ta su buɗe musu ƙofofinta, su ingiza su suna daka musu tsawa tare da tambayar su cewa, wai shin manzanni daga cikinsu ba su je musu ba ne suna karanta musu ayoyin Ubangijinsu, suna kuma tsoratar da su zuwan wannan ranar ta alƙiyama da abin da yake cikinta na azaba mai tsanani? Sai kafirai su yi iƙirari su tabbatar musu da cewa, duk waɗannan abubuwa sun faru, sai dai kuma kalmar azaba ta tabbata a kan kafirai, don haka su ma sun yarda da cewa sun kasance kafirai.
Sai a ƙara yi musu wani wulaƙanci a kan wanda suke ciki inda za a ɗebe musu tsammanin samun rahamar Allah, ko fita daga wuta, a ce da su su shiga ƙofofin Jahannama suna masu dawwama a cikinta har abada, to makomar masu girman kai kuwa ta munana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kyakkyawar tarya da za a yi wa muminai a ranar alƙiyama.

2. Muminai za su shiga Aljanna ƙungiya-ƙungiya, kowa gwargwadon ayyukansa nagari.

3. Tabbatar da cewa Aljanna tana da ƙofofi da kuma mala’iku masu tsaron ta.

4. ‘Yan Aljanna za su dawwama a cikinta har abada.

5. Kyan aiki da nagartarsa shi ne yake haifar da kyakkyawan sakamako ranar alƙiyama.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne wanda ya cancanci yabo da godiya da kirari a duniya da lahira.

Suratuz Zumar (73-75)
وَسِيقَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ رَبَّهُمۡ إِلَى ٱلۡجَنَّةِ زُمَرًاۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا وَفُتِحَتۡ أَبۡوَٰبُهَا وَقَالَ لَهُمۡ خَزَنَتُهَا سَلَٰمٌ عَلَيۡكُمۡ طِبۡتُمۡ فَٱدۡخُلُوهَا خَٰلِدِينَ ٧٣ وَقَالُواْ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي صَدَقَنَا وَعۡدَهُۥ وَأَوۡرَثَنَا ٱلۡأَرۡضَ نَتَبَوَّأُ مِنَ ٱلۡجَنَّةِ حَيۡثُ نَشَآءُۖ فَنِعۡمَ أَجۡرُ ٱلۡعَٰمِلِينَ ٧٤ وَتَرَى ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ حَآفِّينَ مِنۡ حَوۡلِ ٱلۡعَرۡشِ يُسَبِّحُونَ بِحَمۡدِ رَبِّهِمۡۚ وَقُضِيَ بَيۡنَهُم بِٱلۡحَقِّۚ وَقِيلَ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٧٥

73. Aka kuma raka waɗanda suka kiyaye dokokin Ubangijinsu zuwa Aljanna ƙungiya-ƙungiya; har yayin da suka zo wurinta, alhali an bubbuɗe ƙofofinta, kuma masu tsaronta suka ce (da su): “Aminci ya tabbata a gare ku, kun kyautata (ayyukanku), sai ku shige ta kuna masu dawwama.”

74. Suka ce: “Mun gode wa Allah Wanda Ya tabbatar mana da alƙawarinsa, Ya kuma gadar mana da ƙasa muna sauka a Aljanna a duk inda muka ga dama; to madalla da sakamakon masu aiki!”

75. Kuma za ka ga mala’iku suna kewaye da Al’arshi, suna tasbihi da yabon Ubangijnsu; aka kuma yi hukunci a tsakaninsu (halittu) da gaskiya, aka kuma ce: “Yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai.”

A ayoyin ƙarshe na wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suka yi imani suka kiyaye dokokinsa, da cewa, mala’iku za su raka su cikin nutsuwa da girmamawa zuwa gidan Aljanna ƙungiya-ƙungiya. Kafin ma su iso wurinta sun samu mala'iku masu tsaron ta sun riga sun bubbuɗe ƙofofinta, sai su tarye su suna yi musu sallama, suna roƙa musu amincin Allah ya tabbata a gare su, suna kuma yaba musu da cewa zukatansu da ayyukansu sun yi kyau da nagarta, don haka su shiga gidan Aljanna suna masu dawwama a cikinta har abada.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan muminai sun gama shiga gidajensu na Aljanna sai su yi wa Allah godiya su yi masa kirari da cewa, ya cika musu alƙawarin da ya yi musu ta hanyar

manzanninsa na cewa zai shigar da su Aljanna; to ga shi yanzu ya gadar musu da ita, duk inda suka ga damar sauka a cikinta to za su sauka babu mai hana su, don haka suna yi wa junansu sam-barka da sakamakon da Allah ya yi wa masu aiki irin nasu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a wannan rana mala'iku za su zagaye Al'arshi suna tsarkake Allah tare da gode masa da yi masa kirari. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi hukunci na adalci tsakanin halittunsa, ya karrama waɗanda suka cancanci karramawa, ya kuma azabtar da waɗanda suka cancanci azabarsa. A ƙokacin ne za a ce: Yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai game da hukuncinsa na adalci ga kafirai da kuma falalarsa ga muminai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani saukakke ne daga Allah Mabuwayi mai ilimi, ba jiyo shi aka yi ba, kuma ba ƙirƙirarre ne ba. Dalilin ambaton waɗannan siffofi na Allah maɗaukaka, shi ne domin Alƙur'ani ya ƙunshi ma'anonin waɗannan siffofi baki ɗaya, saboda Alƙur'ani ko dai ya zo da bayani game da siffofin Allah da sunayensa da ayyukansa, ko kuma ya zamanto yana ba da labarin abubuwan da suka gabata da wasu masu zuwa. Duk waɗannan sun shiga ƙarƙashin sunansa 'Mai ilimi'. Ko kuma ya zamanto yana ba da labarin wasu manya-manyan ni'imomi ne na Allah ga bayinsa, waɗanda sun shiga ƙarƙashin sunansa 'Ma'abocin ni'imtawa'. Ko kuma ya zamanto yana ba da labarin azabarsa da narkonsa mai tsanani wanda kafirci da saɓon Allah ne sukan jawo su. Wannan kuma ya shiga ƙarƙashin sunansa 'Mai tsananin uƙuba'. Ko kuma ya zamanto yana ba da labarin kasancewar Allah shi ne kaɗai abin bauta na gaskiya tare da bayyana ƙwararan dalilai a kan haka. Waɗannan duk sun shiga ƙarƙashin faɗinsa: "Babu abin bauta da gaskiya sai shi". Ko kuma ya zamana yana ba da labarin ranar alƙiyama da abin da zai faru cikinta na sakamako kyakkyawa da mummuna; wannan kuwa ya tattara ne a ƙarƙashin faɗarsa: "Makoma zuwa gare shi ne."

2. Girman Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda ya siffantu da waɗannan siffofi waɗanda suka ƙunshi kwaɗaitarwa da tsoratarwa, da buɗe wa masu laifuffuka ƙofar tuba da neman gafararsa.

3. Allah yana iya gafarta manyan zunubai da ƙanana gabanin tuba, yana kuma yi wa bawa afuwa game da manyan laifukansa bayan ya tuba.

4. Karɓar tubar bawa da gafarta masa zunubansa wata kyautatawa ce daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba don yin haka ya zama wajibi a kansa ba, domin da a ce wajibi ne a kansa sai ya yi haka, to da ambaton waɗannan siffofi bai zama yabo a gare shi ba.

5. Nuni zuwa ga rinjayar ɓangaren rahamarsa a kan ɓangaren fushinsa, domin ya siffanta kansa da cewa shi mai tsananin uƙuba ne, bayan ya siffanta kansa da wasu siffofi guda biyu masu nuna yalwar rahamarsa.

40-Suratu Ghafir

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da sunan '*Suratu Ghafir*' saboda an siffanta Allah da wannan suna '*Ghafir*' a cikinta a aya ta 3.
Ana kuma kiran ta da '*Suratul Mu'umin*' saboda a cikinta ne kawai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin muminin gidan Fir'auna. Da wannan suna ne Imamul Bukhari da Imamut Tirmizi suka ambace ta a littattafansu.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa Sura ce *Makkiyya*, watau ta sauka gabanin hijira zuwa Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce sura ta sittin (60) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan *Suɾatuz Zumar* kafin *Suratu Fussilat*.

4. Adadin ayoyinta:
Adadin ayoyinta tamanin da biyar ne (85) a lissafin mutanen Sham da na Kufa. A lissafin mutanen Makka da Madina kuwa adadinsu tamanin da huɗu (84) ne. Amma a lissafin mutanen Basra adadinsu tamanin da biyu (82) ne.

5. Babban Jigonta:
Bayanin gwagwarmaya tsakanin ƙarya da gaskiya da kiran masu jayayya da ayoyin Allah zuwa ga imani da gaskiya da watsar da ɓatan da suke a kai don guje wa fushin Allah da azabarsa ta duniya da ta lahira.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Bayanin girman Alƙur'ani da mu'ujizarsa da dalilan da suke tabbatar da cewa shi gaskiya ne kuma daga Allah; masu jayayya da shi suna yi ne kawai don hassada da ƙin gaskiya.
• Wa'azin muminin gidan Fir'auna ya yi kama da wanda Manzon Allah (ﷺ) yake yi wa mushirikai a Makka.
• Dalilai masu ƙarfi waɗanda suke nuna Kaɗaitakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da cancantar a bauta masa shi kaɗai.
• Rushe bautar wanin Allah.
• Tuna wa mutane ni'imomin Allah domin waɗanda ba sa gode masa su gode masa.
• Bayanin dalilan da suke nuna yiwuwar tashi bayan mutuwa.
• Gargaɗin mutane game da ranar alƙiyama da tsorace-tsoracen da ta ƙunsa na dangogin azaba, da nuna cewa babu mai taimakon su a can in ba Allah ba.

• Lallashin Manzon Allah (da kwantar masa da hankali d (ﷺa nuna masa cewa wannan addini shi ne zai yi rinjaye a lokacin rayuwarsa da kuma bayan rasuwarsa.

Suratu Ghafir (1-3)

حمٓ ۝١ تَنزِيلُ ٱلۡكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡعَلِيمِ ۝٢ غَافِرِ ٱلذَّنۢبِ وَقَابِلِ ٱلتَّوۡبِ شَدِيدِ ٱلۡعِقَابِ ذِي ٱلطَّوۡلِۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ إِلَيۡهِ ٱلۡمَصِيرُ ۝٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. HA MIM.

2. Saukarwar Littafi daga Allah ne Mabuwayi, Masani.

3. Mai gafarta zunubi, Mai kuma karɓar tuba, Mai tsananin uƙuba, Mai ni'imatarwa; babu abin bauta wa da gaskiya sai Shi; makoma zuwa gare Shi ne.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da wasu haruffa, kamar yadda ya buɗe wasu surori da irinsu. [Dubi farkon tafsirinmu na *'Suratul Baƙara*' don ƙarin bayani a kansu].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayanin cewa shi Alƙur'ani saukakke ne daga Allah Mabuwayi wanda ya fi ƙarfin kowa da komai kuma masanin maslahohin bayinsa da abin da ya fi dacewa da su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta kansa da cewa shi ne mai gafarta zunuban bayinsa waɗanda suka tuba suka nemi afuwarsa, kuma mai tsananin uƙuba ga duk wanda ya ƙi tuba daga cikinsu; shi ne mai ni'imtawa kuma babu wani abin bauta da gaskiya sai shi kaɗai. Makomar bayi gaba ɗayansu zuwa gare shi ne a ranar alƙiyama inda zai saka wa kowa da irin abin da ya aikata mai kyau ko mummuna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba daidai ba ne bawa ya riƙa zaton cewa idan Allah ya ba wa wani wadata ta duniya wannan alama ce ta yana son sa ko kuma yana kan gaskiya. Abin da ya kamata mutum ya yi la'akari da shi wajen tantance mai gaskiya shi ne dalilai na shari'a da bin hanyar annabawa.

2. Jayayya domin rushe gaskiya da tabbatar da ƙarya bayan hujjoji sun bayyana ƙarara, wannan ɗabi'a ce ta kafirai. Amma jayayya ta hanyar da ta dace, domin bayyana gaskiya da kawar da ruɗani, wannan babu laifi a cikinta, tana ma daga cikin abin da bawa zai kusanci Allah da shi.

3. Gwagwarmaya tsakanin ƙarya da gaskiya daɗaɗɗen al'amari ne, kuma haka za ta ci gaba da faruwa har zuwa tashin alƙiyama.

4. Hallaka da taɓewa su ne ƙarshen duk wata al'umma da ta ƙaryata manzonta, ta yi jayayya don rushe gaskiya.

Suratu Ghafir (4-6)

مَا يُجَٰدِلُ فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَلَا يَغۡرُرۡكَ تَقَلُّبُهُمۡ فِي ٱلۡبِلَٰدِ ۝٤ كَذَّبَتۡ قَبۡلَهُمۡ قَوۡمُ نُوحٖ وَٱلۡأَحۡزَابُ مِنۢ بَعۡدِهِمۡۖ وَهَمَّتۡ كُلُّ
أُمَّةِۢ بِرَسُولِهِمۡ لِيَأۡخُذُوهُۖ وَجَٰدَلُواْ بِٱلۡبَٰطِلِ لِيُدۡحِضُواْ بِهِ ٱلۡحَقَّ فَأَخَذۡتُهُمۡۖ فَكَيۡفَ كَانَ عِقَابِ ۝٥ وَكَذَٰلِكَ حَقَّتۡ كَلِمَتُ رَبِّكَ عَلَى ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ
أَنَّهُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ ۝٦

4. Babu mai yin jayayya game da ayoyin Allah sai waɗanda suka kafirta, saboda haka kada yawan zirga-zirgarsu a garuruwa ya ruɗe ka.

5. Mutanen Nuhu sun ƙaryata kafin su, da kuma ƙungiyoyi (na kafirai) bayansu; kowace al'umma kuma sun yi mummunan nufi da manzonsu don su kama shi (su cutar da shi); suka kuma yi jayayya da (hujja ta) ƙarya don su rusa gaskiya da ita, sai Na kama su; to yaya uƙubata ta kasance?

6. Kamar haka ne kuma kalmar Ubangijinka (ta azaba) ta tabbata a kan waɗanda suka kafirta cewa, lalle su 'yan wuta ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa masu jayayya da ayoyinsa masu nuna Kaɗaitakarsa da gaskiyar manzancin annabawansa su ne waɗanda suka kafirce masa, saboda gurɓacewar hankulansu, don haka kada Manzon Allah ya nuna damuwarsa a kansu, kada kuma zirga-zirgarsu ta kasuwanci gari da gari da arzikin da Allah ya ba su ya ruɗe shi, ko ya ɗaga masa hankali; wannan ba komai ba ne, talala ce kawai Allah yake yi musu, amma ƙarshensu ba zai yi kyau ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) game da ƙaryata shi da kafirai suke yi, da cewa ba shi ne farau ba game da haka, domin mutanen Annabi Nuhu gabaninsu sun ƙaryata Manzonsu Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kuma ƙungiyoyin kafirai da suka zo bayansa su ma sun ƙaryata annabawansu, kamar Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanen Madyana da Fir'auna da jama'arsa, duk sun ƙaryata manzanninsu. Kowace al'umma daga cikinsu kuma sun yi yunƙurin su kama manzonsu su kashe shi, amma Allah bai ba su sa'a ba. Kuma sun yi jayayya da hujja ta ƙarya don su rushe gaskiya da ita; to amma daga ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya damƙi waɗannan al'ummu gaba ɗayansu ya kuma hallaka su. Sai Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya duba ya ga yadda uƙubarsa gare su ta kasance. Babu shakka azaba ce mai tsananin gaske.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Manzonsa (ﷺ) cewa, to kamar yadda ya hukunta waɗannan al'ummu da suka ƙaryata gaskiya suka ja da manzanninsa, haka kalmarsa ta azaba ta tabbata ga kafirai cewa, su 'yan wuta ne ba makawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jin daɗi yana cika ne da abubuwa biyu, girmama umarnin Allah da tausaya wa bayin Allah.

2. Gabatar da tasbihi da yabo ga Allah a kan neman gafara ga bayin Allah, yana nuna ana gabatar da girmama umarnin Allah a kan tausaya wa bayinsa.

3. Falalar imani da ta muminai, shi ya sa mala'iku suke shagala da yi musu addu'o'i na ƙwarai da nema musu gafarar Allah.

4. Kwaɗaitarwa a kan yi wa muminai addu'a da nema musu gafara a bayan idonsu. Wannan ɗabi'a ce ta masu tausaya wa bayin Allah, domin koyi da mala'ikun Allah. Muɗarrif ɗan Abdullahi ɗan Shikkhir yana

cewa: “Mun kula cewa waɗanda suka fi cutar da bayin Allah su ne shaiɗanu, waɗanda kuma suka fi kyautata musu su ne mala’iku.” Sannan ya karanta waɗannan ayoyi.

5. Imani da Allah shi ne babbar alaƙar da ta haɗa tsakanin mala’ikun Allah da suke sama da muminai da suke ƙasa.

6. Yalwar rahamar Allah wadda ta mamaye sammai da ƙasa.7. Yalwar ilimin Allah wanda ya kewaye komai da kowa a sama da ƙasa.

8. Addu’ar mala’iku ta ƙunshi abubuwa masu yawa. Daga cikinsu akwai:
a. Cikakken sani da mala’iku suka yi wa Ubangijinsu, da tawassulinsu da sunayensa mafiya kyau da yake son bayinsa su riƙa kama ƙafa da su zuwa gare shi.
b. Cikakken ladabinsu ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yayin da suka yi iƙrari da gamammiyar Rububiyyarsa da keɓantacciya, suka nuna cewa su ba su mallaki komai a hannunsu ba sai abin da ya ba su, don haka su masu buƙata ne a wajensa.
c. Sun nuna ƙaunarsu ga abin da Allah yake so na kyawawan ayyuka da masu yin su, watau muminai masoya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Ghafir (7-9)
ٱلَّذِينَ يَحۡمِلُونَ ٱلۡعَرۡشَ وَمَنۡ حَوۡلَهُۥ يُسَبِّحُونَ بِحَمۡدِ رَبِّهِمۡ وَيُؤۡمِنُونَ بِهِۦ وَيَسۡتَغۡفِرُونَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْۖ رَبَّنَا وَسِعۡتَ كُلَّ شَيۡءٖ رَّحۡمَةٗ وَعِلۡمٗا فَٱغۡفِرۡ لِلَّذِينَ تَابُواْ وَٱتَّبَعُواْ سَبِيلَكَ وَقِهِمۡ عَذَابَ ٱلۡجَحِيمِ ٧ رَبَّنَا وَأَدۡخِلۡهُمۡ جَنَّٰتِ عَدۡنٍ ٱلَّتِي وَعَدتَّهُمۡ وَمَن صَلَحَ مِنۡ ءَابَآئِهِمۡ وَأَزۡوَٰجِهِمۡ وَذُرِّيَّٰتِهِمۡۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٨ وَقِهِمُ ٱلسَّيِّـَٔاتِۚ وَمَن تَقِ ٱلسَّيِّـَٔاتِ يَوۡمَئِذٖ فَقَدۡ رَحِمۡتَهُۥۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٩

7. Waɗanda suke ɗauke da Al’arshi da waɗanda suke kewaye da shi suna yin tasbihi da yabon Ubangijinsu, suna kuma yin imani da Shi, kuma suna nema wa waɗanda suka yi imani gafara, (suna cewa): “Ya Ubangiijnmu, ka yalwaci kowane abu da rahama da ilimi, to Ka gafarta wa waɗanda suka tuba suka kuma bi hanyarka, Ka kuma kiyaye su daga azabar (wutar) Jahimu.

8. “Ya Ubangijinmu, Ka kuma shigar da su gidajen Aljannar zama waɗanda ka alƙawarta musu, tare da waɗanda suke salihai daga iyayensu da matayensu da kuma zuriyarsu. Lalle Kai Mabuwayi ne, Mai hikima.

9. “Ka kuma kiyaye su munanan (ayyuka). Duk kuwa wanda Ka kiyaye shi daga munanan (sakamako) a wannan rana, haƙiƙa Ka yi masa rahama. Wannan kuwa shi ne babban rabo.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna yadda mala’aikunsa suke ƙaunar muminai suke yi musu addu’o'i na ƙwarai a ko da yaushe da cewa mala’ikun da suke ɗauke da Al’arshinsa da waɗanda suke kewaye da shi suna tsarkake shi daga duk wani abu da bai dace da shi ba tare da yabon sa, suna kuma yin imani da shi, suna kuma roƙa wa waɗanda suka yi imani da Allah gafara, suna tawassuli da yabon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda rahamarsa da iliminsa sun yalwaci komai, domin ya gafarta wa muminai da suka tuba suka bi hanyarsa ta gaskiya, a kan ya tsare su daga azabar wuta.
Suna kuma roƙon sa da ya shigar da muminai gidajen Aljanna na zama har abada waɗanda ya yi musu alƙawari zai shigar da su, ya shigar da su tare da dukkan iyayensu da matansu da ‘ya’yansu waɗanda ayyukansu suka yi kyau. Saboda shi ne Mabuwayi wanda babu mai rinjayar sa, mai hikima cikin duk abin da ya halitta ko ya ƙaddara ya tsara.

Mala’iku suka ci gaba da roƙa wa muminai Allah kan ya tsare su daga aikata munanan ayyuka da zai azabta su da su, domin duk wanda ya kuɓutar a ranar alƙiyama daga uƙubar munanan ayyukansa, to lalle ya yi masa rahama, wannan kuwa shi ne babban rabo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son imani da aikin alheri daga bayinsa, yana kuma ƙi musu kafirci da sharri. Fushin da Allah zai yi wa kafirai da ƙiyayyarsa gare su lokacin da ake yi musu azaba sun fi waɗanda suke yi wa kawunansu na cewa, sun biye wa soye-soyen zukatansu har suka jefa su ramin ɓata da hallaka.

2. Iƙirarin da kafirai za su yi na laifukansu da yardarsu cewa sun cancanci azaba, wannan ba zai amfana musu komai a wurin Allah ba.

3. Abin da ya jawo wa kafirai hallaka da azaba shi ne bijire wa imani da Allah da manzanninsa da kafirce wa ranar lahira da fifita shirka da saɓon Allah a kan imani da ɗa’a ga Allah.

Suratu Ghafir (10-12)
إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُنَادَوۡنَ لَمَقۡتُ ٱللَّهِ أَكۡبَرُ مِن مَّقۡتِكُمۡ أَنفُسَكُمۡ إِذۡ تُدۡعَوۡنَ إِلَى ٱلۡإِيمَٰنِ فَتَكۡفُرُونَ ١٠ قَالُواْ رَبَّنَآ أَمَتَّنَا ٱثۡنَتَيۡنِ وَأَحۡيَيۡتَنَا ٱثۡنَتَيۡنِ فَٱعۡتَرَفۡنَا بِذُنُوبِنَا فَهَلۡ إِلَىٰ خُرُوجٖ مِّن سَبِيلٖ ١١ ذَٰلِكُم بِأَنَّهُۥٓ إِذَا دُعِيَ ٱللَّهُ وَحۡدَهُۥ كَفَرۡتُمۡ وَإِن يُشۡرَكۡ بِهِۦ تُؤۡمِنُواْۚ فَٱلۡحُكۡمُ لِلَّهِ ٱلۡعَلِيِّ ٱلۡكَبِيرِ ١٢

10. Lalle waɗanda suka kafirta ana kiran su cewa: “Tabbas fushin Allah da ku ya fi girman fushinku ga kawunanku, lokacin da ake kiran ku zuwa imani (a duniya) sai kuke kafircewa.”

11. Suka ce: “Ya Ubangijinmu, Ka kashe mu sau biyu Ka kuma raya mu sau biyu, to mun amsa laifukanmu, shin ko akwai wata hanya ta fita (daga wuta)?”

12. Wannan (sakamakon) saboda cewa, idan aka kira Allah Shi kaɗai sai ku kafirce, idan kuwa aka yi shirka da Shi, sai ku yi imani. To hukuncin na Allah ne Maɗaukaki, Mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa kafirai cewa a ranar alƙiyama za a kira su domin a shigar da su wutar Jahannama suna faman zargin kawunansu da jin haushin kansu; a lokacin za a faɗa musu cewa, tsananin fushin da Allah yake yi da su ya fi wanda suke yi wa kansu, yayin da a duniya ake kiran su su yi imani da Allah sai suka kafirce masa suka riƙa bauta wa wasu gumaka ba shi ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa furucin da zai riƙa fita daga bakunansu a lokacin shi ne za su riƙa cewa, ya kashe su sau biyu, watau a da babu su sai ya samar da su, sannan ya kashe su lokacin cikar ajalinsu. Ya kuma raya su sau biyu, watau lokacin da ya samar da su bayan a da babu su, sannan bayan mutuwarsu ya sake tashin su domin yi musu hisabi, suka kuma fito fili suka amsa laifukan da suka aikata a rayuwarsu ta duniya. To amma yanzu suna tambaya ne wai ko akwai wata hanya ta komawa duniya don su gyara ayyukansu su nemi yardar Allah?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa abin da ya jawo musu shiga wannan hali na takaici da mummunar azaba shi ne, tun a duniya idan an kira Allah shi kaɗai ba a haɗa shi da komai ba sai su kafirce masa su sanya masa kishiyoyi, amma idan an bauta wa wani tare da Allah sai su yi imani. Allah ya tabbatar musu da cewa hukunci nasa ne shi kaɗai, domin shi ne Maɗaukaki da Zatinsa da siffarsa da ikonsa, kuma mai girma wanda kowa da komai a ƙarƙashin ikonsa yake.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar Allah da luɗufinsa ga bayinsa, yayin da ya samar musu da ayoyi da hujjoji bayyanannu masu nuna samuwarsa da Kaɗaitakarsa da cikakkiyar Kudurarsa, domin ya shiryar da su. Daga waɗannan ayoyi da hujjoji akwai waɗanda suke abubuwa ne da jiki yake buƙata, kamar ruwan sama da abin da zuciya take buƙata, kamar kyautatuwar imani da addini.

2. Komawa ga Allah da yi masa ɗa'a su ne suke sanya bawa ya wa'azantu da ayoyin Allah; shirka da saɓon Allah kuma su suke toshe basira su bice hasken hankali. Idan kuwa bawa ya koma ga Allah ya bi dokokinsa sai wannan shamakin ya yaye idanu su ga hanyar tsira tar.

3. Wajabcin tsantsanta addu'a da sauran ibadu ga Allah shi kaɗai ko da kuwa kafirai ba sa so.

Suratu Ghafir (13-17)

هُوَ ٱلَّذِى يُرِيكُمْ ءَايَٰتِهِۦ وَيُنَزِّلُ لَكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ رِزْقًا ۚ وَمَا يَتَذَكَّرُ إِلَّا مَن يُنِيبُ ﴿١٣﴾ فَٱدْعُوا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿١٤﴾
رَفِيعُ ٱلدَّرَجَٰتِ ذُو ٱلْعَرْشِ يُلْقِى ٱلرُّوحَ مِنْ أَمْرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ لِيُنذِرَ يَوْمَ ٱلتَّلَاقِ ﴿١٥﴾ يَوْمَ هُم بَٰرِزُونَ ۖ لَا يَخْفَىٰ عَلَى ٱللَّهِ مِنْهُمْ
شَىْءٌ ۚ لِّمَنِ ٱلْمُلْكُ ٱلْيَوْمَ ۖ لِلَّهِ ٱلْوَٰحِدِ ٱلْقَهَّارِ ﴿١٦﴾ ٱلْيَوْمَ تُجْزَىٰ كُلُّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْ ۚ لَا ظُلْمَ ٱلْيَوْمَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلْحِسَابِ ﴿١٧﴾

13. Shi ne wanda Yake nuna muku ayoyinsa, Yake kuma saukar muku da arziki daga sama (watau ruwan sama). Ba kuma kowa ne yake wa'azantuwa ba sai mai komawa (ga Allah).

14. Sai ku bauta wa Allah kuna masu tsantsanta addini gare Shi, ko da kuwa kafirai ba sa so.

15. (Shi ne) Mai maɗaukakan darajoji, Ma'abocin Al'arshi, Yana sauko da wahayi daga umarninsa ga wanda Ya ga dama daga bayinsa don Ya yi gargaɗin ranar haɗuwa.

16. Ranar da za su bayyana; babu wani abu nasu da zai ɓuya ga Allah. (Zai ce): "Mulki na wane ne a yau?" (Sai Ya ce): "Na Allah Makaɗaici, Mai rinjaye ne."

17. A wannan ranar za a saka wa kowane rai da irin abin da ya aikata. Babu zalunci a wannan ranar. Lalle Allah Mai gaggawar yin hisabi ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi ne yake nuna wa mutane dalilan Kudurarsa da Kaɗaitakarsa a cikin sasannin sama da kuma a kawunansu, dalilai masu nuna cancantar a bauta masa shi kaɗai kada a yi shirka da shi. Shi ne kuma wanda yake saukar musu da ruwa daga sama wanda a sanadiyyarsa suke samun arziki na tsirrai da shuke-shuke; to amma babu mai wa'azantuwa da irin waɗannan ayoyi nasa sai wanda yake komawa ga Allah, ya tuba ya tsantsanta bautarsa gare shi shi kaɗai. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su roƙe shi suna masu tsantsanta addu'arsu da ibadarsu gare shi shi kaɗai, kada su haɗa wani da shi ko da kuwa kafirai ba sa son haka.

Abdullahi ɗan Zubairu (Allah ya ƙara masa yarda) ya kasance bayan kowace salla idan ya yi sallama yana cewa: "Babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, mulki nasa ne, yabo ma nasa ne, shi kuma mai iko ne a kan komai. Babu wata ɗabara babu wani ƙarfi sai tare da Allah. Babu abin bauta da gaskiya sai shi, ba za mu bauta wa kowa ba sai shi kaɗai. Ni'ima da falala nasa ne, kuma yana da kyakkyawan yabo. Babu abin bauta da gaskiya sai shi, muna masu tsantsanta addini gare shi ko da kafirai

ba sa so.” Ya ce: “Annabi (ﷺ) ya kasance yana ɗaga muryarsa da faɗar waɗannan kalmomi bayan kowace salla.” [Muslim #594].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta kansa da wasu siffofi guda uku:
Siffa ta ɗaya, shi ne mai maɗaukakan darajoji, watau yana sama da kowa, kowa da komai ƙasa suke da shi.
Ta biyu, ma’abocin Al’arshi, mai girma wanda yake a ƙololuwar sama.
Ta uku, yana saukar da wahayinsa ga wanda ya ga dama daga bayinsa, domin su rayu, kuma su raya wasunsu da shi, su kuma tsoratar da mutane da zuwan ranar alƙiyama wadda a cikinta ne za a haɗa halittun farko da na ƙarshe wuri guda domin yi musu hisabi da sakamako.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta wannan rana da cewa, ita ce ranar da duk halittu za su bayyana su tattaru a farfajiyar ƙasa ɗaya, babu wani abu da zai ɓoye wa Allah, su kansu ko ayyukansu. Zai yi tambaya a wannan ranar da cewa mulki na wane ne? A ƙokacin amsa ɗaya ce tak, mulki na Allah ne, Makaɗaici a Zatinsa da siffofinsa da ayyukansa, mai rinjaye wanda ya fi ƙarfin kowa, kuma kowa da komai sun rusuna masa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta kansa da cikakken adalci, da cewa, a ranar za a cika wa kowane rai sakamakon aikinsa mai kyau ko mummuna, don kuwa a ranar ba za a zaluntar kowa, domin mai hukunci a ranar shi ne Allah mai cikakken adalci. Allah kuma tabbas mai gaggawar yi wa bayinsa hisabi ne domin saninsa ya kewaye komai.

An karɓo daga Abu Zarrin (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: ‘Ya ku bayina, lalle ni na haramta wa kaina zalunci, na kuma sanya shi haramun a tsakaninku, don haka kada ku zalunci junanku…’ har zuwa inda Allah ya ce: ‘Ya ku bayina, ayyukanku ne kawai nake ƙididdige muku su, sannan in cika muku sakamakonsu. To wanda ya sami alheri sai ya gode wa Allah, wanda kuwa ya sami saɓanin haka, to kada ya zargi kowa sai kansa.’” [Muslim #2577]

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kusantowar alƙiyama da tsananin abin da ta ƙunsa na firgici da ban tsoro.

2. Azzalumai ba su da wani aboki ko ɗan’uwa ko mai ceto da zai cece su a ranar alƙiyama.

3. Ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya game komai da kowa. Duk yadda aka ɓoye kowane abu ne, to Allah yana sane da shi. Wannan gargaɗi ne da zaburarwa a kan aikata aikin alheri komai ƙanƙantarsa da guje wa mummunan aiki komai ƙanƙantarsa, domin Allah yana sane da shi kuma zai yi sakayya a kansa.

4. Cikar adalcin Allah cikin dukkan hukunce-hukuncensa na shari’a ko na ƙaddara.

5. Duk wani abin bauta ba Allah ba, to gajiyayye ne ba zai iya amfanar mai bautar sa da komai ba.

Suratu Ghafir (18-20)
وَأَنذِرۡهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡأٓزِفَةِ إِذِ ٱلۡقُلُوبُ لَدَى ٱلۡحَنَاجِرِ كَٰظِمِينَۚ مَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ حَمِيمٖ وَلَا شَفِيعٖ يُطَاعُ ١٨ يَعۡلَمُ خَآئِنَةَ ٱلۡأَعۡيُنِ وَمَا تُخۡفِي ٱلصُّدُورُ ١٩ وَٱللَّهُ يَقۡضِي بِٱلۡحَقِّۖ وَٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ لَا يَقۡضُونَ بِشَيۡءٍۗ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ٢٠

18. Ka kuma tsoratar da su ranar (alƙiyama) mai kusantowa, a yayin da zukata suke maƙare a wuyoyinsu (saboda tsananin tsoro). Azzalumai ba su da wani masoyi ko kuma wani mai ceto da za a yi wa biyya.

19. (Allah) Yana sane da ha’incin idanuwa da kuma abin da zukata suke ɓoyewa.

20. Allah Yana hukunci da gaskiya; waɗanda kuwa suke bauta wa wanda ba Shi ba, ba sa hukunta komai. Haƙiƙa Allah Shi ne Mai ji, Mai gani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya gargaɗi kafirai ya tsoratar da su zuwan ranar alƙiyama wadda take tafe ba da daɗewa ba. Ya sanar da su cewa ita rana ce da take cike da abubuwan ban tsoro da firgici; domin saboda tsananin firgicin da ke cikinta zukata za su yunƙuro su yiwo sama har zuwa ga maƙoshi, watau kamar za su fito don tsananin razana, duk mutane kuma za su yi tsit babu wani mai iya cewa uffan sai wanda Allah ya yi masa izini. Azzalumai kuma waɗanda suka mutu suna shirka da saɓon Allah ba su da wani aboki ko makusanci ko wani mai ceto da za a yarda da shi a amince da cetonsa gare su.
Allah kuma yana sane da duk wani ha’inci na idanu masu satar kallon abin da ya haramta su kalla, yana kuma sane da duk abin da zukata suke ɓoyewa, babu wani abu da zai ɓuya gare shi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shi ne yake hukunci na gaskiya da adalci, babu wanda zai zalunta ya rage masa ladan kyawawan ayyukansa, ko ya kama shi da laifin da bai aikata ba. To amma abubuwan da mushirikai suke bauta wa ba Allah ba, ba sa iya hukunta komai, domin ba su mallaki komai ba, kuma ba za su iya taɓuka komai ba, shi kuwa Allah mai jin maganganun bayinsa ne, kuma mai ganin duk ayyukansu da niyyoyinsu ne, zai kuma yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tafiya mabuɗin ilimi ce da wa’azantuwa daga abubuwan da ido zai gani na ayoyin Allah.

2. Mai hankali shi ne wanda yake ɗaukar darasi daga wanda ya gabace shi.

3. Tsananin ƙarfin halitta da ƙarfin arzuki da raya ƙasa da gine-gine da gonaki, ba za su kare mutane daga azabar Allah ba idan ta zo musu saboda yawan zunubansu.

4. Al’ummun da suka gabata sun fi na yanzu ƙarfin ƙirar jiki da tasiri a bayan ƙasa.

5. Duk wanda Allah ya yi nufin yi masa azaba, to babu mai iya kare shi.

6. Duk wanda ya yi imani da cewa Allah ne mai ƙarfi, to ba zai dogara da ƙarfinsa ko wayonsa ba, zai mayar masa da al’amarinsa ne baki ɗaya.

Suratu Ghafir (21-22)
*أَوَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ كَانُواْ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَانُواْ هُمۡ أَشَدَّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗ وَءَاثَارٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ بِذُنُوبِهِمۡ وَمَا كَانَ لَهُم مِّنَ ٱللَّهِ مِن وَاقٖ ٢١ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ كَانَت تَّأۡتِيهِمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَكَفَرُواْ فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُۚ إِنَّهُۥ قَوِيّٞ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٢٢

21. Shin ba sa tafiya a bayan ƙasa sannan su ga yaya ƙarshen waɗanda suka kasance gabaninsu ya zama? Su sun kasance sun fi su tsananin ƙarfi da barin gurabe na tarihi a bayan ƙasa, sai Allah Ya kama su da laifukansu, ba su kuma da wani mai kare su daga Allah.

22. Wannan (ya same su ne) saboda manzanninsu sun kasance suna zuwa musu da hujjoji bayyanannu, sai suka kafirce, sai Allah Ya kama su. Lalle Shi Mai (tsananin) ƙarfi ne, Mai tsananin azaba.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da kafirai azabar lahira, sai kuma ya tsoratar da su azabar duniya da cewa, shin ba su yawata a bayan ƙasa ba ne domin su gane wa idanuwansu irin yadda ƙarshen al'ummun da suka gabace su waɗanda suka ƙaryata annabawansu ya kasance? Domin kuwa sun yi mummunan ƙarshe duk da cewa sun zarce waɗannan mushirikan da tsananin ƙarfi, sun kuma bar alamu na gine-gine da gonaki a bayan ƙasa fiye da yadda waɗannan mushirikai suka yi, to amma duk da haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su saboda zunubansu, kuma ba su da wani wanda zai kare su daga azabar Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa azabarsa ta saukar wa al'ummun da suka gabata ne, saboda manzanninsa sun yi ta zuwa musu da ƙarfafan hujjoji bayyanannu, amma sai suka kafirce, suka ƙaryata manzanninsu, sai Allah ya damƙe su ya hallaka su duk kuwa da irin ƙarfin da suke taƙama suna da shi, domin Allah mai tsananin ƙarfi ne Buwayi, kuma mai tsananin uƙuba ne ga duk wanda ya kafirce masa ya kuma ƙaryata manzanninsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An ambaci Fir'auna da Hamana da Karuna su kaɗai, domin su ne manyan jagororin kafirci da faɗa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sauran maƙiya duk mabiyansu ne.

2. Jifan masu ƙoƙarin kawo gyara a cikin al'umma da munanan siffofi don mutane su guje su, wata tsohuwar al'ada ce ta maɓarnata, domin su hana gaskiya ta samu karɓuwa a cikin al'umma, su kuma ci gaba da cin karensu babu babbaka.

3. Amfani da ƙarfi shi ne hanya ta ƙarshe da azzalumai suke bi yayin da ƙaryarsu ta ƙare, suka fara jin tsoron kada gaskiya ta yi halinta.

4. Fir'auna har bayan aiko Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sake ba da umarni a karo na biyu a ci gaba da kisan 'ya'ya maza na Banu Isra'ila, a bar matansu domin ya ci gaba da gallaza musu, ya kuma rage adadinsu don kada su yi ƙarfi su raba shi da mulkinsa.

5. Duk yadda maɓarnata suka kai wajen shirya wa masu gaskiya mugun tanadi da ƙoƙarin kawar da gaskiya da razana masu riƙe da ita, ba za su taɓa cin nasara ba; ƙarshensu zai lalace a banza.

6. Tsananin rashin kunyar Fir'auna, wai shi da yake kashe jarirai da bautar da mata da azabtar da Banu Isra'ila da tsare su, shi ne yake jin tsoron kada Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ɓatar da mutane ko kuma ya haddasa fitina da ɓarna a cikinsu, watau yana nuna ya fi Annabi Musa tausayi da son zaman lafiya da gyara al'umma.

7. Hanyar da ta fi dacewa don neman kariya daga sharrin mai sharri, ita ce neman mafaka a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai da dogaro gare shi.

8. Abubuwa biyu sukan sanya mutum ya riƙa cutar da jama'a: Na farko, idan shi mai girman kai ne, mai ƙeƙasasshiyar zuciya; na biyu, idan bai yi imani da ranar alƙiyama ba, don haka bai yarda akwai wani hisabi ba tsakaninsa da waɗanda ya cuta, to wannan ne zai mayar da shi babban macuci.

9. Fir'auna ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) izgili yayin da ya ce da shi ya kira Ubangijinsa. Sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna masa cewa gaskiya ne shi mai

roƙon Ubangijinsa ne don ya kare shi daga sharrinsa, Allah kuma ya karɓa masa addu'arsa ya tserar da shi da jama'arsa daga makircin Fir'auna da rundunarsa.

Suratu Ghafir (23-27)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا وَسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٍ ٢٣ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَ وَقَٰرُونَ فَقَالُواْ سَٰحِرٞ كَذَّابٞ ٢٤ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلۡحَقِّ مِنۡ عِندِنَا قَالُواْ ٱقۡتُلُوٓاْ أَبۡنَآءَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ وَٱسۡتَحۡيُواْ نِسَآءَهُمۡۚ وَمَا كَيۡدُ ٱلۡكَٰفِرِينَ إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ ٢٥ وَقَالَ فِرۡعَوۡنُ ذَرُونِيٓ أَقۡتُلۡ مُوسَىٰ وَلۡيَدۡعُ رَبَّهُۥٓۖ إِنِّيٓ أَخَافُ أَن يُبَدِّلَ دِينَكُمۡ أَوۡ أَن يُظۡهِرَ فِي ٱلۡأَرۡضِ ٱلۡفَسَادَ ٢٦ وَقَالَ مُوسَىٰٓ إِنِّي عُذۡتُ بِرَبِّي وَرَبِّكُم مِّن كُلِّ مُتَكَبِّرٖ لَّا يُؤۡمِنُ بِيَوۡمِ ٱلۡحِسَابِ ٢٧

23. Haƙiƙa kuma Mun aiko Musa da ayoyinmu da kuma hujja mabayyaniya.

24. Zuwa ga Fir'auna da Hamana da Karuna, sai suka ce shi mai sihiri ne, babban maƙaryaci.

25. To lokacin da ya zo musu da gaskiya daga wajenmu sai suka ce: "Ku kashe `ya`yan waɗanda suka yi imani tare da shi, ku kuma ƙyale matansu da rai." Makircin kafirai bai zama ba sai a lalace.

26. Fir'auna kuma ya ce: "Ku bar ni in kashe Musa, kuma (ya je) ya kirawo Ubangijin nasa; lalle ni ina jin tsoron kada ya sauya addininku ko kuma ya bayyanar da ɓarna a bayan ƙasa."

27. Musa ya ce: "Lalle ni ina neman tsari da Ubangijina, da kuma Ubangijinku daga duk wani mai girman kai da ba ya yin imani da ranar hisabi."

A nan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa labarin wasu al'ummun da suka ƙaryata annabawansu ne ya kuma saukar musu da azabarsa, don ya zama gargaɗi ga mutanensa da cewa, ya aiko da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ayoyinsa bayyanannu da ƙarfafan hujjoji masu tabbatar da ingancin manzancinsa, ya kuma aike shi ne zuwa ga Fir'auna da Wazirinsa Hamana da kuma Karuna. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana musu ƙwararan dalilai da suke tabbatar da manzancinsa da gaskiyar abin da ya zo musu da shi. Yayin da Fir'auna da jama'arsa suka kasa kawo wata hujja don su kare kansu sai kawai suka ce, ai Annabi Musa mai sihiri ne, kuma babban maƙaryaci, ba manzo ne daga Allah ba.
Daga nan ne fa Fir'auna ya ba wa zabaniyawansa umarni cewa, su kashe dukkan 'ya'ya maza na ƙabilar Banu Isra'ila waɗanda suka yi imani da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), su ƙyale 'ya'yansu mata, domin su ci gaba da tozarta su da bautar da su a gidajensu ta hanyar saka su aikatau na wulaƙanci. Duk kuma suna yin haka ne domin su hana mutane karɓar gaskiya da kuma rage yawan Banu Isra'ila ƙabilar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), amma ba su san cewa makircin da Fir'auna yake ƙullawa duk a banza zai ƙare ba, babu wani tasiri da zai yi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Fir'auna bai tsaya a kan kashe 'ya'yan Banu Isra'ila kaɗai ba, har ma sai da ya shiga yi wa Annabi Musa barazanar zai kashe shi, yana nuna kamar wasu ne suke dakatar da shi, shi kuma yana barazanar cewa su ƙyale shi ya gama da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), wai kuma in ya isa to ya roƙi Ubangijinsa da ya ce shi ne ya aiko shi, ya zo ya kare shi ya hana wani abu ya same shi. Fir'auna ya bayyana wa mutanensa dalilin da ya sa yake son kashe Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa, wai shi yana jin tsoron kada ya sauya musu addininsu wanda ya same su suna a kai na bautar wanin Allah, ya shigar da su addininsa na bautar Allah ɗaya, ko kuma ya bayyanar da wata ɓarna a bayan ƙasa, watau ya kawo rikici da saɓani tsakanin mutane wanda zai haifar musu da yamutsi da kashe-kashe.

To lokacin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sami labarin barazanar da Fir’auna yake yi masa, sai ya roƙi Allah Ubangijinsa kuma Ubangijin Fir’auna da jama’arsa da ya tsare shi daga makircin duk wani mai girman kai mai ƙin gaskiya wanda ya ƙi yin imani da ranar lahira irin Fir’auna da jama’arsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin ɓoye imani domin cim ma wata babbar maslaha ko guje wa wata cutuwa.

2. Muhimmancin siffantuwar mai kira zuwa ga Allah da ƙarfin imani, domin wannan yana yin tasiri matuƙa a kan waɗanda yake kira, sannan zai taimaka masa wajen ƙarin ilimi da imani a zukatansu.

3. Yana da kyau mai kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zama mutum mai ƙarfin hali marar tsoro.

4. Abu ne mai muhimmancin gaske mai kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi amfani da kusancinsa ga masu riƙe da madafun iko wajen yaɗa da’awarsa da taimakon ‘yan’uwansa masu da’awa.

5. Wajibi ne a kan duk wani mai kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kada ya yi ƙasa a gwiwa wajen isar da gaskiya zuwa ga rukunan mutane na al’umma daban-daban; masu mulki da talakawansu, ya kuma yi amfani da salon da ya dace wajen kiran kowane rukuni na mutane.

6. Barazanar kisa ko ɗauri ko azabtarwa wani daɗaɗɗen salo ne da azzalumai suke amfani da shi don yaƙar masu faɗar gaskiya, don haka yana da matuƙar muhimmanci mai kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗauki matakin da ya dace don guje wa cutuwa ga kansa ko ga da’awarsa.

7. Wajibi ne yin amfani da hujjoji na hankali yayin tattaunawa da mutanen da ba su yi imani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ko manzancin annabawa ba, kamar mulhidai masu kore samuwar Allah.

8. Hanya mafi inganci ta da’awa ita ce amfani da salon kwaɗaitarwa da na tsoratarwa a lokaci guda, domin haka shi zai nuna cewa mai kira zuwa ga Allah yana son shiriyar mutane ne, don su sami kyakkyawan sakamako su kuma kuɓuta daga azabar Allah.

9. Mai ƙoƙarin gyara jama’arsa yana da kyau ya riƙa nuna musu cewa shi ma ɗaya ne daga cikinsu, duk abin da zai faranta musu rai shi ma zai yi farin ciki da shi, abin da kuma zai baƙanta musu to shi ma zai baƙanta masa; wannan zai sanya su ɗauki maganganunsa da muhimmanci sosai.

10. Azabar Allah da fushinsa sun fi kusa da masu riƙe da madafun iko masu faɗa a ji a cikin al’umma, don haka su ne ya fi dacewa su shiga taitayinsu, su guji saɓon Allah.

Suratu Ghafir (28-29)

وَقَالَ رَجُلٞ مُّؤۡمِنٞ مِّنۡ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ يَكۡتُمُ إِيمَٰنَهُۥٓ أَتَقۡتُلُونَ رَجُلًا أَن يَقُولَ رَبِّيَ ٱللَّهُ وَقَدۡ جَآءَكُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ مِن رَّبِّكُمۡۖ وَإِن يَكُ كَٰذِبٗا فَعَلَيۡهِ كَذِبُهُۥۖ وَإِن يَكُ صَادِقٗا يُصِبۡكُم بَعۡضُ ٱلَّذِي يَعِدُكُمۡۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَنۡ هُوَ مُسۡرِفٞ كَذَّابٞ ٢٨ يَٰقَوۡمِ لَكُمُ ٱلۡمُلۡكُ ٱلۡيَوۡمَ ظَٰهِرِينَ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَمَن يَنصُرُنَا مِنۢ بَأۡسِ ٱللَّهِ إِن جَآءَنَاۚ قَالَ فِرۡعَوۡنُ مَآ أُرِيكُمۡ إِلَّا مَآ أَرَىٰ وَمَآ أَهۡدِيكُمۡ إِلَّا سَبِيلَ ٱلرَّشَادِ ٢٩

28. Kuma wani mutum mumini daga dangin Fir’auna wanda yake ɓoye imaninsa ya ce: “Yanzu kwa kashe mutum don ya ce ‘Allah ne Ubangijina’, kuma alhalin ya zo muku da hujjoji bayyanannu daga Ubangijinku? Idan ya zama maƙaryaci ne to laifin ƙaryarsa yana kansa; idan kuwa ya zama mai gaskiya, to wani abu daga

abin da yake yi muku gargaɗinsa zai same ku. Lalle Allah ba Ya shiryar da wanda yake shi mai yawan ɓarna ne, maƙaryaci.

29. “Ya ku mutanena, a yau ku ne masu mulki masu ƙarfi a bayan ƙasa, to wane ne zai kare mu daga azabar Allah idan ta zo mana?” Fir’auna ya ce: “Ba abin da nake nuna muku sai abin da na gani (shi ne daidai), kuma hanyar shiriya kaɗai nake nuna muku.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin luɗufin da ya yi wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan ya roƙe shi ya kuɓutar da shi daga sharrin Fir’auna, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hore masa hanyoyin samun kuɓuta, daga cikinsu ya kimsa imani cikin zuciyar ɗaya daga cikin dangin Fir’auna wanda ya riƙa ɓoye imaninsa da Allah da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don tsoron kada Fir’auna ya hallaka shi, sai ya tashi ya nuna wa mutanensa rashin dacewar a kashe Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa, yanzu yaya za a kashe mutumin da bai yi wani laifi ba sai don kawai ya ce Allah ne Ubangijinsa, kuma ya zo musu da hujjoji da ƙarfafan dalilai waɗanda suke tabbatar da gaskiyar cewa shi Manzon Allah ne? Watau ya nuna musu cewa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai furta wata magana ba da har zai cancanci uƙubar ƙisa.
Wannan mutum mumini kuma ya kawo musu wata hujja ta hankali wadda duk mai hankali zai gamsu da ita da cewa, da za a ce Annabi Musa maƙaryaci ne, to ai a kansa ƙaryar za ta ƙare, watau kansa kaɗai zai cutar ba zai cutar da kowa ba. Kuma idan ya kasance mai gaskiya ne, to tabbas sai wata azaba da yake musu alƙawarin zuwanta ta auka musu ba da daɗewa ba idan ba su yi imani ba. Sannan ya tabbatar musu da cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya shiryar da mutumin da yake mai yawan ƙetare iyakokinsa, mai yi masa ƙarya ya yi wa manzanninsa.
Mutumin nan ya sake kiran mutanensa Kibɗawa ya gargaɗe su da cewa, a yau su ne masu mulki da ƙarfi a ƙasar Masar, to amma su yi tunani su gane cewa wane ne zai taimake su ya kare su daga azabar Allah idan ta zo musu yayin da suka kashe Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi)? Watau yana nuna musu cewa shi ma ɗaya ne daga cikinsu, duk abin da ya same su to shi ma zai same shi.
To bayan Fir’auna ya saurari nasihohin wannan mutum mumini, sai ya yi biris da duk abin da ya ji, ya kuma nuna wa mutanensa cewa shi mai matuƙar son su da alheri ne, kuma ba zai taɓa ɗora su a kan hanyar da ba daidai ba, don haka su yarda da cewa mafita kawai ita ce a bar shi ya kashe Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kowa ya huta, domin maganarsa ita kaɗai ce kan hanya wadda ya wajaba dukkansu su amince da ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tuna wa mutane labarin al’ummun farko da Allah ya hallaka, wata babbar hanya ce ta faɗakarwa da jan hankali.

2. Shiriya tana hannun Allah ne shi kaɗai.

3. Mutanen Masar ba su yi imani da saƙon Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba; sun yi ta shakku ne da tantama game da shi. To bayan ya rasu sai suka riƙa nuna farin cikinsu da rasuwarsa har ma suna furta cewa Allah ba zai sake aiko da wani manzo ba bayansa.

4. Ketare iyakokin Allah da kafirci da yawan saɓon Allah da nuna shakka game da gaskiya sukan hana bawa samun shiriya daga Allah.

5. Jayayya domin rushe gaskiya da tabbatar da ƙarya mummunar ɗabi’a ce ta ɓatattun mutane.

6. Girman kai yana hana mai shi karɓar gaskiya.

Suratu Ghafir (30-35)

وَقَالَ ٱلَّذِىٓ ءَامَنَ يَٰقَوۡمِ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُم مِّثۡلَ يَوۡمِ ٱلۡأَحۡزَابِ ٣٠ مِثۡلَ دَأۡبِ قَوۡمِ نُوحٖ وَعَادٖ وَثَمُودَ وَٱلَّذِينَ مِنۢ بَعۡدِهِمۡۚ وَمَا ٱللَّهُ يُرِيدُ ظُلۡمٗا لِّلۡعِبَادِ ٣١ وَيَٰقَوۡمِ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ يَوۡمَ ٱلتَّنَادِ ٣٢ يَوۡمَ تُوَلُّونَ مُدۡبِرِينَ مَا لَكُم مِّنَ ٱللَّهِ مِنۡ عَاصِمٖۗ وَمَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنۡ هَادٖ ٣٣ وَلَقَدۡ جَآءَكُمۡ يُوسُفُ مِن قَبۡلُ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَمَا زِلۡتُمۡ فِي شَكّٖ مِّمَّا جَآءَكُم بِهِۦۖ حَتَّىٰٓ إِذَا هَلَكَ قُلۡتُمۡ لَن يَبۡعَثَ ٱللَّهُ مِنۢ بَعۡدِهِۦ رَسُولٗاۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ مَنۡ هُوَ مُسۡرِفٞ مُّرۡتَابٌ ٣٤ ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ بِغَيۡرِ سُلۡطَٰنٍ أَتَىٰهُمۡۖ كَبُرَ مَقۡتًا عِندَ ٱللَّهِ وَعِندَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْۚ كَذَٰلِكَ يَطۡبَعُ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ قَلۡبِ مُتَكَبِّرٖ جَبَّارٖ ٣٥

30. Sai kuma wannan da ya yi imani ya ce: “Ya ku mutanena, lalle ni ina jiye muku tsoron irin ranar gangamin ƙungiyoyin (kafirai).

31. “Kamar misalin al’adar mutanen Nuhu da Adawa da Samudawa da kuma waɗanda suka zo bayansu. Allah kuwa ba Ya nufin zalunci ga bayi.

32. “Kuma ya ku mutanena, lalle ni ina jiye muku tsoron ranar kiraye-kirayen juna (ranar alƙiyama).

33. “Ranar da za ku juya kuna masu ba da baya, ba ku da wani mai kare ku daga Allah. Duk kuma wanda Allah Ya ɓatar to ba shi da wani mai shiryarwa.”

34. Haƙiƙa kuma Yusufu ya zo muku da (hujjoji) bayyanannu tun kafin (zuwan Musa), to ba ku gushe kuna kokwanton abin da ya zo muku da shi ba, har yayin da ya mutu sai kuka ce: “Allah ba zai sake aiko da wani manzo bayansa ba.” Kamar haka ne Allah Yake ɓatar da duk wanda shi mai ɓarna ne, mai shakka.

35. Waɗanda suke yin jayayya game da ayoyin Allah ba tare da wata hujja da ta zo musu ba; ƙyamar (wannan) a wurin Allah da wurin waɗanda suka yi imani ta girmama. Kamar haka ne Allah Yake toshe zuciyar duk wani mai girman kai, mai tsaurin rai.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana nasihar muminin gidan Fir’auna ga mutanensa bayan ya ji ra’ayin Fir’auna da kafewarsa a kan mummunan ra’ayinsa, duk kuwa da irin hujjoji na hankali da ya kawo masa. Wannan bawan Allah ya ci gaba da yi musu nasiha yana nuna musu cewa idan suka kuskura suka kashe Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) to yana jiye musu tsoron irin azabar da ta auka wa al’ummun da suka ƙaryata manzanninsu a baya su ma ta same su, Allah ya hallaka su kamar yadda ya hallaka waɗancan, kamar yadda ya yi wa mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Samudawa mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka zo bayansu, duk sun kafirce wa Allah sun kuma ƙaryata manzanninsa sai Allah ya hallaka su baki ɗayansu domin kuwa sun cancanci haka. Allah kuma ba ya nufin zaluntar wani daga cikin bayinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wannan bawan Allah ya sake kiran mutanensa ya ja hankalinsu game da ranar alƙiyama wadda yake jiye musu tsoronta, da cewa ita rana ce da mutane za su yi ta kiran junansu saboda dangantaka ta jini, ko saboda neman wata alfarma, suna tsammanin yin haka zai amfane su ya fitar da su daga tashin hankalin wannan ranar, amma ina sun makara.

Ya kuma tabbatar musu cewa a ranar duk za su juya a guje domin tsere wa wutar Jahannama, amma babu wani wanda zai kare su daga azabar Allah. Ya kuma nuna musu cewa shiriya ta Allah ce, duk kuwa wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya taɓar da shi to ba shi da wanda zai iya shiryar da shi.
Sannan ya tuna musu labarin Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Allah ya aiko shi zuwa kakanninsu da irin taurin kan da suka nuna masa, da cewa Annabi Yusufu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo musu da hujjoji bayyanannu masu nuna Kaɗaitakar Allah, to amma sun dage suna a kan shakkar gaskiyar abin da ya zo musu da shi, har ma sai bayan ya rasu shakkarsu game da gaskiyarsa ta daɗa ƙaruwa, suka ma fito fili suka ce wai bayansa Allah ba zai sake aiko wani manzo ba. Sai ya tabbatar musu cewa, da irin wannan ɓata nasu ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ɓatar da duk wani mai ƙetare iyakokinsa mai shakka game da Kaɗaitakarsa.
Sannan ya bayyana siffar masu irin wancan hali da cewa su ne waɗanda suke jayayya da ayoyin Allah don su rushe su ba tare da wata hujja ko wani dalili da ya zo musu ba. Kiyayyar jayayyarsu ta girmama a wurin Allah da wurin waɗanda suka yi imani da shi da manzanninsa.
Ya tabbatar musu cewa wannan ita ce sunnar Allah a kansu da ire-irensu, watau ya toshe zukatansu alheri ya kasa shiga cikinsu, kamar yadda yake toshe zuciyar duk wani mai girman kai mai fariya wanda ya ƙi gaskiya bayan ta bayyana gare shi da ƙarfafan hujjoji.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk lokacin da maƙaryaci ya rasa hujjar kamawa sai ya shiga hayaniya da kawo ruɗu da izgili, don ya yi nasarar hana sauran mutane fahimtar gazawarsa wajen kare abin da yake kai.

2. Yana daga cikin manyan musibu da za su iya samun mutum, a ƙawata masa ƙarya har ya riƙa ganin ta kyakkyawa ya dage wajen ba ta kariya da jayayya da masu sukan ta, ya riƙa kuma yaɗa ta bainar jama'a.

3. Duk wata dabara da maƙiya gaskiya za su fito da ita don danne gaskiya ba za su taɓa yin nasara ba har abada.

Suratu Ghafir (36-37)
وَقَالَ فِرۡعَوۡنُ يَٰهَٰمَٰنُ ٱبۡنِ لِي صَرۡحَا لَّعَلِّيٓ أَبۡلُغُ ٱلۡأَسۡبَٰبَ ٣٦ أَسۡبَٰبَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ فَأَطَّلِعَ إِلَىٰٓ إِلَٰهِ مُوسَىٰ وَإِنِّي لَأَظُنُّهُۥ كَٰذِبٗاۚ وَكَذَٰلِكَ زُيِّنَ لِفِرۡعَوۡنَ سُوٓءُ عَمَلِهِۦ وَصُدَّ عَنِ ٱلسَّبِيلِۚ وَمَا كَيۡدُ فِرۡعَوۡنَ إِلَّا فِي تَبَابٖ ٣٧

36. Fir'auna kuma ya ce: "Ya Hamana, ka gina min dogon gini ko na kai ga hanyoyi.

37. "(Watau) hanyoyin (da ke kaiwa zuwa) sammai sai in gano Ubangijin Musa, lalle kuma ni ina tsammaninsa maƙaryaci ne." Kamar haka kuma aka ƙawata wa Fir'auna mummunan aikinsa aka kuma kange shi daga hanyar (gaskiya). Makircin Fir'auna kuwa ba a komai yake ba sai cikin halaka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda taurin kan Fir'auna ya tsananta bayan ya ji wa'azin da muminin nan ya yi masa, har ta kai shi ga kiran Wazirinsa Hamana ya umarce shi da ya gina masa wani dogon gini wanda zai hau kansa ko zai sami hanyoyin da za su ɓulle da shi cikin sammai, wai don ya gano abin bautar Annabi Musa wanda ya faɗa masa cewa shi ne abin bauta na gaskiya. Sai kuma ya dawo yana cewa shi fa yana zaton Annabi Musa ƙarya yake faɗa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar haka ne aka ƙawata wa Fir'auna mummunan aikinsa, aka kuma kautar da shi daga bin hanyar gaskiya ya kama bin hanyar ɓata wanda hakan ya sanya shi irin wancan mugun tunani da

mummunan tanadi don ya rusa gaskiya ya tabbatar da ƙarya, bai san cewa makircinsa ba a bakin komai yake ba sai asara da taƀewa, domin ƙarshensa shi ne taƀarƀarewa da lalacewa da tsiya ta har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi game da ruɗuwa da ƙyale-ƙyalen duniya da mantawa da lahira. Mai hankali kuma shi yake fifita abu mai wanzuwa da ɗorewa a kan abin da zai yanke ya ƙare.

2. Yalwar rahamar Allah da falalarsa ga bayinsa da cikar adalcinsa yayin da yake saka wa mai laifi da gwargwadon laifinsa, amma wanda ya yi aiki nagari sai ya ninninka masa ladansa fiye da aikinsa.

3. Namiji da mace duk ɗaya suke wajen yin imani da ayyuka nagari, babu mai fin wani sai wanda ya fi tsoron Allah.

4. Babu mai shiga Aljanna sai mai imani.

5. Kafirci da shirka da saƀon Allah hanya ce ta zuwa wuta, don haka duk wanda ya yi kira zuwa gare su to yana kira ne zuwa ga shiga wuta.

6. Muhimmancin dogaro ga Allah da mayar da al'amari gare shi ga mai kira zuwa ga Allah, domin da haka ne zai samu cim ma buƙatarsa da kuma kare kansa daga duk wata cuta.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne mai tsare bayinsa na ƙwarai daga sharrin masu sharri.

8. Duk wanda ya yi niyyar cutar da bayin Allah nagari to kansa makircinsa zai koma.

9. Tabbatar da azabar ƙabari ga kafirai. Sunnar Manzon Allah (ﷺ) kuma ta tabbatar da ita ga Musulmin da suka mutu suna saƀon Allah.

10. Azabar lahira ta fi kowace azaba tsanani da bala'i.

Suratu Ghafir (38-46)

وَقَالَ ٱلَّذِىٓ ءَامَنَ يَٰقَوۡمِ ٱتَّبِعُونِ أَهۡدِكُمۡ سَبِيلَ ٱلرَّشَادِ ۝٣٨ يَٰقَوۡمِ إِنَّمَا هَٰذِهِ ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا مَتَٰعٞ وَإِنَّ ٱلۡأٓخِرَةَ هِىَ دَارُ ٱلۡقَرَارِ ۝٣٩ مَنۡ عَمِلَ سَيِّئَةٗ فَلَا يُجۡزَىٰٓ إِلَّا مِثۡلَهَاۖ وَمَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَأُوْلَٰٓئِكَ يَدۡخُلُونَ ٱلۡجَنَّةَ يُرۡزَقُونَ فِيهَا بِغَيۡرِ حِسَابٖ ۝٤٠ ۞وَيَٰقَوۡمِ مَا لِيٓ أَدۡعُوكُمۡ إِلَى ٱلنَّجَوٰةِ وَتَدۡعُونَنِيٓ إِلَى ٱلنَّارِ ۝٤١ تَدۡعُونَنِي لِأَكۡفُرَ بِٱللَّهِ وَأُشۡرِكَ بِهِۦ مَا لَيۡسَ لِي بِهِۦ عِلۡمٞ وَأَنَا۠ أَدۡعُوكُمۡ إِلَى ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡغَفَّٰرِ ۝٤٢ لَا جَرَمَ أَنَّمَا تَدۡعُونَنِيٓ إِلَيۡهِ لَيۡسَ لَهُۥ دَعۡوَةٞ فِي ٱلدُّنۡيَا وَلَا فِي ٱلۡأٓخِرَةِ وَأَنَّ مَرَدَّنَآ إِلَى ٱللَّهِ وَأَنَّ ٱلۡمُسۡرِفِينَ هُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ ۝٤٣ فَسَتَذۡكُرُونَ مَآ أَقُولُ لَكُمۡۚ وَأُفَوِّضُ أَمۡرِيٓ إِلَى ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ بَصِيرُۢ بِٱلۡعِبَادِ ۝٤٤ فَوَقَىٰهُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِ مَا مَكَرُواْ وَحَاقَ بِـَٔالِ فِرۡعَوۡنَ سُوٓءُ ٱلۡعَذَابِ ۝٤٥ ٱلنَّارُ يُعۡرَضُونَ عَلَيۡهَا غُدُوّٗا وَعَشِيّٗاۚ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ أَدۡخِلُوٓاْ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ أَشَدَّ ٱلۡعَذَابِ ۝٤٦

38. Sai (mutumin nan) wanda ya yi imani ya ce: "Ya ku mutanena, ku bi ni in nuna muku hanyar shiriya.

39. "Ya ku mutanena, lalle wannan rayuwar ta duniya ɗan jin daɗi ne, kuma lalle lahira ita ce gidan tabbata.

40. “Wanda ya aikata wani mummunan aiki, to ba za a saka masa ba sai da kwatankwacinsa, wanda kuwa ya aikata wani kyakkyawan aiki, namiji ne ko mace alhali shi yana mumini, to waɗannan za su shiga Aljanna, a riƙa arzuta su a cikinta ba tare da lissafi ba.

41. “Kuma ya ku mutanena, me ya sa ne nake kiranku zuwa ga tsira, ku kuma kuke kira na zuwa wuta?

42. “Kuna kira na da in kafirce wa Allah, in kuma tara Shi da abin da ba ni da wani sani a kansa, ni kuma ina kiran ku zuwa Mabuwayi, Mai yawan gafara?

43. “Ba shakka abin da kuke kira na zuwa gare shi ba shi da wani kira karɓaɓɓe a duniya ko a lahira, kuma lalle makomarmu zuwa ga Allah ne, maɓarnata kuma tabbas su ne ‘yan wuta.

44. “To ba da daɗewa ba za ku tuna abin da nake gaya muku. Ina kuma miƙa al’amarina zuwa ga Allah. Lalle Allah Mai ganin bayi ne.”

45. Sai Allah Ya kiyaye shi (sakamakon) mummunan abin da suka shirya; kuma mummunar azaba ta saukar wa mutanen Fir’auna.

46. (Ita ce) wuta da za a riƙa bijirar da su a gare ta safe da yamma; Ranar tashin alƙiyama kuma za a ce: “Ku shigar da mutanen Fir’auna mafi tsananin azaba.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da faɗa mana wa’azin muminin gidan Fir’auna yayin da ya ga taurin kan Fir’auna da jama’arsa yana ta ƙaruwa, sai ya sake kiran mutanensa cewa su yarda su bi shi, zai nuna musu hanyar shiriya, watau yana nufin su yi watsi da ƙaryar da Fir’auna yake faɗa musu cewa, ba ya nuna musu komai sai hanyar shiriya.
Ya ja hankalinsu game da biye wa ƙyale-ƙyalen rayuwar duniya, da cewa ita rayuwa ce ta jin daɗi kaɗan mai yankewa, don haka kada su kuskura su bari ta ruɗe su; su gane cewa lalle gidan lahira da ni’imomin da ke cikinta su ne tabbas waɗanda ba za su gushe ba har abada. Don haka su tashi tsaye su yi aiki domin samun rayuwar lahira mai ɗorewa su guji ruɗin duniya.
Sai ya faɗakar da su game da adalcin Allah da girman rahamarsa da kuma falalarsa ga mutane da cewa, duk wanda ya yi mummunan aiki, to sakamakonsa daidai da gwargwadon laifinsa ne, amma wanda ya yi kyakkyawan aiki don Allah, namiji ne shi ko mace, alhali kuma ya yi imani da Allah da manzanninsa, to masu irin waɗannan siffofi su ne za su shiga Aljanna ranar alƙiyama inda za a riƙa arzuta su da abubuwan da ke cikinta na kayan marmari su yi ta more rayuwa ta jin daɗi marar yankewa ba tare da lissafi ba.
Sannan ya fito fili ya bayyana wa mutanensa imaninsa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya ci gaba da kiran su tare da nuna mamakinsa game da yadda shi yake ta kiran su zuwa ga hanyar tsira daga asarar duniya da ta lahira ta hanyar yin imani da Allah da aiki nagari, amma su kuma suna kiran sa zuwa ga shiga wuta ta ƙoƙarin tunkuɗa shi cikin kafirci da shirka da Allah da saɓon sa.
Ya ci gaba da jaddada maganar da yake faɗa musu da cewa, tabbas abin da suke kiran sa da ya yi imani da shi ba shi da wani burbushin gaskiya a duniya ko a lahira, kuma shi ba zai taɓa amsa kiran duk wanda ya kira shi ba, sannan makomarsu gaba ɗaya zuwa ga Allah take shi kaɗai; maɓarnata a ranar kuma su ne ‘yan wuta waɗanda za su dawwama a cikinta har abada.
Sannan ya rufe nasiharsa da tsoratar da su mummunan ƙarshensu idan har sun bijire wa abin da yake faɗa musu da cewa, akwai ranar da za ta zo su tuna irin nasihar da yake yi musu, su yi nadamar rashin karɓar nasiharsa a lokacin da nadamar ba za ta yi musu amfani ba. Ya bayyana musu cewa shi dai ya mayar da dukkan al’amuransa ga Allah shi kaɗai, domin Allah yana ganin komai na ayyukan bayinsa, ya kuma san halin da yake ciki na rauni da rashin mataimaki mai kare shi idan sun yi niyyar cutar da shi.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya tsare wannan mumini daga mummunan makircin da suka shirya na kashe shi; shi kuma Fir'auna da mutanensa mummunar azaba ta auka musu yayin da aka nutsar da su cikin ruwa suka hallaka baki ɗayansu. Sannan kuma bayan wannan azabar a ranar alƙiyama za a ci gaba da bijirar da su a kan wuta safe da yamma, kuma a ba da umarnin shigar da su matsananciyar azaba saboda kafircinsu da saɓon Allah da suka dinga yi a nan duniya.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan ɗayanku ya mutu za a riƙa nuna masa mazauninsa safe da yamma, idan shi ɗan Aljanna ne, to daga mazauninsa na 'yan Aljanna, idan kuma shi ɗan wuta ne, to daga masaukinsa na 'yan wuta, sai a ce masa: 'Wannan shi ne masaukinka har Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tashe ka zuwa gare shi ranar alƙiyama.' [Bukhari #1379 da Muslim #2866].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kasancewar mutum mai rauni ne a nan duniya ba shi da iko da kansa sai yadda shugabanninsa suka yi da shi, don haka sai ya bi su a kan kafirci da saɓon Allah, wannan ba zai hana a saka shi wuta tare da su ba, domin ai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi hankali da kuma damar ya zaɓi abin da yake gaskiya ya bi, to amma sai ya yi watsi da wannan damar ya yarda ya zama ɗan amshin Shata, ya bi Yarima ya sha kiɗa, don haka kada ya zargi kowa sai kansa.

2. Wanda ya bi wasu manya a kan ɓata yana zaton za su amfane shi a lahira, to ya sani ba za su amfana wa kansu komai ba ballantana shi su amfane shi da wani abu.

3. Duk shugabannin ɓata a duniya za su yi baram-baram da mabiyansu a lahira, za su nuna musu cewa su ma ta kansu suke ba za su tsinana musu komai ba, don kuwa babu wani sauran iko a hannunsu.

4. Azabar kafirai a wutar Jahannama mai ɗorewa ce babu ƙaƙƙautawa ko da daidai da rana ɗaya, don haka suke magiya suna roƙon mala'iku masu tsaron wuta su sa baki su roƙa musu Allah ya sassauta musu don su ɗan sarara ko da yini ɗaya ne, amma ina, hakan ba za ta samu gare su ba.

Suratu Ghafir (47-50)
وَإِذۡ يَتَحَآجُّونَ فِي ٱلنَّارِ فَيَقُولُ ٱلضُّعَفَٰٓؤُاْ لِلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُوٓاْ إِنَّا كُنَّا لَكُمۡ تَبَعٗا فَهَلۡ أَنتُم مُّغۡنُونَ عَنَّا نَصِيبٗا مِّنَ ٱلنَّارِ ٤٧ قَالَ ٱلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُوٓاْ
إِنَّا كُلّٞ فِيهَآ إِنَّ ٱللَّهَ قَدۡ حَكَمَ بَيۡنَ ٱلۡعِبَادِ ٤٨ وَقَالَ ٱلَّذِينَ فِي ٱلنَّارِ لِخَزَنَةِ جَهَنَّمَ ٱدۡعُواْ رَبَّكُمۡ يُخَفِّفۡ عَنَّا يَوۡمٗا مِّنَ ٱلۡعَذَابِ ٤٩ قَالُوٓاْ أَوَ لَمۡ
تَكُ تَأۡتِيكُمۡ رُسُلُكُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ قَالُواْ بَلَىٰۚ قَالُواْ فَٱدۡعُواْۗ وَمَا دُعَٰٓؤُاْ ٱلۡكَٰفِرِينَ إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ ٥٠

47. (Ka tuna) kuma lokacin da suke ta yin jayayya a cikin wuta, sai raunanan su riƙa ce wa waɗanda suka yi girman kai: "Lalle mun kasance mabiyanku (a duniya), to shin za ku iya ɗauke mana wani kaso na (azabar) wuta?"

48. Waɗanda suka yi girman kai sai su ce: "Lalle mu duka a cikinta muke, lalle Allah Ya riga Ya yi hukunci tsakanin bayi."

49. Kuma waɗanda suke cikin wuta suka ce da masu tsaron Jahannama: "Ku roƙa mana Ubangijinku mana Ya saukake mana azaba ta wuni (ɗaya)."

50. Suka ce: “Yanzu manzanninku ba su kasance suna zo muku da (ayoyi) bayyanannu ba?” Suka ce: “Haka ne (sun zo)”. Sai su ce: “To sai ku yi ta roƙon. Roƙon kafirai kuwa bai zamo ba sai a taɓe.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzo (ﷺ) da ya tuna lokacin da ‘yan wuta za su kaure da jayayya tsakanin shugabanni da mabiyansu, inda raunanan mabiyan za su riƙa yi wa manyansu ƙorafi cewa su fa mabiyansu ne a duniya, domin su ne suka ingiza su cikin ɓata, to shin yanzu za su iya ɗauke musu wani kaso na azabar Allah da suke ciki? Sai su kuma manyan masu girman kani su amsa musu da cewa, ai a wannan rana babu wani shugaba ko wani mabiyi, dukkansu suna cikin wutar ne, don haka zancen wani ya ɗauke wa wani azaba bai taso ba, domin kuwa Allah ne kaɗai mai yin hukunci a ranar, to ya riga ya yi hukunci tsakanin bayinsa, ya ba wa kowa kasonsa na azaba da ya cancance shi.
Bayan su duka sun gane babu mai iya taimakon wani daga cikinsu, sai suka koma suna roƙon mala’iku masu tsaron wutar Jahannama don su roƙa musu Allah da ya sassauta musu tsananin azabar da suke ciki ko da na yini guda ne kacal ko za su samu su sarara. Nan take sai mala’iku su mayar musu da martani cewa, ashe manzanninsu ba su zo musu da hujjoji da dalilai bayyanannu ba? Sai kafirai su amsa da cewa, lalle kam an yi haka, watau dai son zuciya ne da taurin kai kawai ya hana su yin imani. Sai mala’ikun su amsa musu cikin gatsali da tsokana cewa, ai sai su dage su yi ta addu’a suna roƙon Allah ko sa sami biyan buƙata, amma ai addu’ar kafirai bayan sun shiga wuta a banza take ba ta da wani amfani gare su, don sun riga sun zo lahira suna shirka ba su tuba ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙawarin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) na nasararsa da taimakonsa ga manzanninsa da muminai a kan maƙiyansu a duniya da lahira.

2. Babbar karramawar da Allah zai yi wa bayinsa nagari, watau annabawa da mabiyansu da sauran muminai ita ce wadda zai yi musu a ranar da zai tara duk halittunsa na farko da na ƙarshe, watau ranar lahira.

3. Allah ba zai taɓa karɓar hanzarin mushirikai ba a ranar alƙiyama.

4. Babbar baiwar da Allah ya yi wa Banu Isra’ila ta saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) littafin Attaura wanda ya ƙunshi shiriya da ilimi mai amfani da wa’azi, ya kuma gadar da shi ga Banu Isra’ila ‘ya’ya da jikoki domin masu hankali daga cikinsu su ci gaba da amfana da haskensa.

5. Mutane masu lafiyayyen hankali su ne koyaushe sukan amfana da wa’azi da tunatarwa a cikin kowace al’umma.

6. Wajabcin yin haƙuri da muhimmancinsa wajen fuskantar ƙarya da ma’abotanta.

7. Neman gafara, da tasbihi tare da gode wa Allah, su ne muhimman guzuri da tafiya a kan tafarkin Allah take buƙata.

Suratu Ghafir (51-55)
إِنَّا لَنَنصُرُ رُسُلَنَا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَيَوۡمَ يَقُومُ ٱلۡأَشۡهَٰدُ ٥١ يَوۡمَ لَا يَنفَعُ ٱلظَّٰلِمِينَ مَعۡذِرَتُهُمۡۖ وَلَهُمُ ٱللَّعۡنَةُ وَلَهُمۡ سُوٓءُ ٱلدَّارِ ٥٢
وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡهُدَىٰ وَأَوۡرَثۡنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱلۡكِتَٰبَ ٥٣ هُدٗى وَذِكۡرَىٰ لِأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٥٤ فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ
وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ بِٱلۡعَشِيِّ وَٱلۡإِبۡكَٰرِ ٥٥

51. Lalle Mu tabbas Muna taimakon manzanninmu da kuma waɗanda suka yi imani a rayuwar duniya da kuma ranar da shedu za su tsaya.

52. Ranar da hanzarin azzulamai ba zai amfane su ba; la'ana kuma ta tabbata a kansu, suna kuma da mummunan gida.

53. Kuma haƙiƙa Mun bai wa Musa shiriya, Muka kuwa gadar wa Banu-Isra'ila littafin (Attaura).

54. Don shiriya da wa'azantuwa ga masu hankali.

55. Sai ka yi haƙuri, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne, ka kuma nemi gafarar zunubinka, kuma ka yi tasbihi da yabon Ubangijinka a maraice da safiya.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gama ba da labarin Fir'auna da mabiyansa da makomarsu a duniya da lahira, sai ya bayyana irin nasara da yake ba wa manzanninsa da mabiyansu a nan duniya da kuma lahira, ya tabbatar da cewa zai taimaka musu ta hanyar bayyana hujjarsu a fili ga kowa, zai kuma ba su nasara a kan abokan gabarsu, sannan a lahira zai yi musu rahama ya shigar da su Aljanna; maƙiyansu kuma ya ɗanɗana musu uƙuba a wutar Jahannama, bayan annabawa da mala'iku da muminai sun ba da shaidar cewa, saƙon Allah ya isa gare su amma suka kafirce suka ƙi yin imani da manzanninsu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wannan ranar ita ce ranar da hanzarin waɗanda suka zalunci kawunansu da shirka da kafirci da saɓon Allah ba zai amfane su da komai ba, domin la'anar Allah ta tabbata a kansu, ba su babu samun rahamar Allah, kuma suna da mummunan gida na azaba mai raɗaɗi, watau Jahannama.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ɓangare na taimakonsa ga manzanninsa da muminai a nan duniya, da cewa, ya bai wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shiriya, watau ilimin da Banu Isra'ila za su samu shiriya da shi, ya kuma sanya Attaura littafi ne da za su ci gaba da gadar sa 'ya'ya da jikoki. Littafi ne na shiriya da wa'azantuwa ga mutane masu hankali, domin ya ƙunshi hukunce-hukuncen shari'a, yana kuma kwaɗaitarwa game da aikin alheri da tsawatarwa a kan aikin sharri.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya ƙara haƙuri game da ƙaryatawar da mutanensa suke yi masa da tsangwamar da suke nuna masa shi da sahabbansa, ya tabbatar masa da cewa, alƙawarin da ya yi masa na ba shi nasara shi da mabiyansa muminai gaskiya ne babu kokwanto a cikinsa, sai dai kawai ya ci gaba da ƙara ƙarfafa dangantakarsa da Ubangijinsa, ya nemi gafarar zunubansa, ya kuma yi ta tasbihi tare da gode wa Ubangijinsa safe da yamma.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman kai da neman ɗaukaka su ne suka sanya wasu mutane maƙiya gaskiya suna yin jayayya da ita, da ƙoƙarin kawo ruɗani da rikici don su lalata ta, to amma haƙansu ba zai taɓa cim ma ruwa ba.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk mai jayayya da gaskiya don tabbatar da ƙarya ƙarshensa wulaƙanci da tozarta ba zai taɓa samun nasara ba har abada.

3. Halittar sammai da ƙasa tana tabbatar da yiwuwar dawo da matattu da ransu, domin duk wanda ya iya halittar babban abu irinsu mai iko ne ya halicci wanda bai kai su girma ba.

4. Kafiri da mumini ba za su taɓa zama ɗaya ba a wurin Allah, don haka bambanta tsakaninsu wajen soyayya da girmamawa wajibi ne.

5. Kusantowar ranar alƙiyama kuma zuwanta abu ne da babu makawa.

Suratu Ghafir (56-59)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ بِغَيۡرِ سُلۡطَٰنٍ أَتَىٰهُمۡ إِن فِي صُدُورِهِمۡ إِلَّا كِبۡرٞ مَّا هُم بِبَٰلِغِيهِۚ فَٱسۡتَعِذۡ بِٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ٥٦ لَخَلۡقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ أَكۡبَرُ مِنۡ خَلۡقِ ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٥٧ وَمَا يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَلَا ٱلۡمُسِيٓءُۚ قَلِيلٗا مَّا تَتَذَكَّرُونَ ٥٨ إِنَّ ٱلسَّاعَةَ لَأٓتِيَةٞ لَّا رَيۡبَ فِيهَا وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يُؤۡمِنُونَ ٥٩

56. Lalle waɗanda suke yin jayayya game da ayoyin Allah ba tare da wata hujja da ta zo musu ba, ba komai a cikin zukatansu sai neman ɗaukaka wadda ba za su same ta ba. Sai ka nemi tsari daga Allah; lalle Shi Mai ji ne, Mai gani.

57. Tabbas halittar sammai da ƙasa ta fi girma a kan halittar mutane, sai dai kuma yawancin mutane ba sa sanin (haka).

58. Kuma makaho da mai gani ba za su yi daidai ba, kuma waɗanda suka yi imani suka yi aiki nagari ba za su yi (daidai) da mai mummunan aiki ba. Kaɗan ne ƙwarai kuke wa'azantuwa.

59. Lalle alƙiyama tabbas za ta zo babu kokwanto a cikinta, sai dai kuma yawancin mutane ba sa yin imani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, duk masu jayayya da ayoyinsa don ganin sun rusa, su sun tabbatar da ƙarya ba tare da wata hujja ko wani ƙwaƙƙwaran dalili ba, to babu abin da yake sanya su irin wannan mummunan aiki sai girman kai da neman ɗaukaka da ya mamaye zukatansu. Kuma ba za su sami hakan ba sai dai su gamu da ƙaskanci da wulaƙanci. Don haka sai ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya nemi tsarin Allah daga duk wani sharri na mutum ko aljani, domin shi Allah mai jin maganganun bayinsa ne mai ganin ayyukansu, zai kuma yi wa kowa sakayya a kan abin da ya aikata mai kyau ko mummuna.
Daga cikin irin jayayyar da mushirikai suka riƙa yi wa Manzon Allah (ﷺ), akwai batun tashi bayan mutuwa, suna ganin abu ne da ba zai yiwu ba, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kafa musu hujjar yiwuwar hakan da dalilin da duk wani mai hankali ba ya da ja a kansa, watau halittar sammai da ƙasa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa tabbas halittar sammai da ƙasa ta fi girma a kan halittar mutane. Don haka wanda ya halicce su da wannan girman nasu da yalwarsu ta yaya za a ce ba zai iya dawo da halittar mutane ba bayan mutuwarsu? Tabbas duk mai hankali zai gamsu da cewa yin haka ga Allah abu ne mai matuƙar sauƙi, to amma kuma yawancin mutane ba sa gane hakan ballantana ya zamo musu hujja a kan tashin matattu bayan mutuwa, duk kuwa da cewa abu ne a fili.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana bambancin mumini da kafiri wajen fahimtar ayoyin Allah da gane hujjojin cikar Kudurarsa da cewa, makaho da mai gani ba za su yi daidai ba, hakanan waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa suka kyautata ayyukansu ba za su taɓa zama daidai da wanda ya munana aikinsa da aƙidarsa ba, to amma kuma 'yan kaɗan ne a cikin mutane suke gane haka har su wa'azantu su yi ƙoƙarin shiga cikin shiryayyu waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa suka kyautata ayyukansu.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa lalle ranar alƙiyama tabbas tana nan tafe babu makawa, a lokacin ne zai tashi matattu domin yin hisabi da sakamako, amma duk da haka yawancin mutane ba su yi imani da zuwan wannan rana ba, don haka suka ƙi yi mata kowane irin tanadi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cewa addu’a ibada ce, don haka ba ya halatta a fuskantar da ita ga wani ba Allah ba.

2. Duk wanda girman kai ya hana shi roƙon Allah, to lalle zai shiga wutar Jahannama a wulaƙance a ranar alƙiyama.

3. Babban abin mamaki shi ne yadda wasu suke bijire wa imani da Allah da kaɗaita shi da bauta, duk kuwa da cewa ga dalilai a fili masu tabbatar da cikar Kudurarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai.

4. Tunatar da ɗan’adam ni’imar da ke tattare da samuwar dare da yini waɗanda yake mantawa da su, ba ya yi wa Allah godiya a kansu, saboda yana ganin su suna maimaituwa kullum, sai wannan ya shagaltar da shi, duk kuwa da cewa su manyan dalilai ne masu tabbatar da Ɗayantakar Allah da cikar Kudurarsa.

5. Kafa hujja da Rububiyyar Allah game da Uluhiyyarsa.

6. Jayayya da ayoyin Allah shi ya ja wasu suka faɗa cikin bautar wanin Allah.

Suratu Ghafir (60-65)

وَقَالَ رَبُّكُمُ ٱدۡعُونِيٓ أَسۡتَجِبۡ لَكُمۡۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسۡتَكۡبِرُونَ عَنۡ عِبَادَتِي سَيَدۡخُلُونَ جَهَنَّمَ دَاخِرِينَ ٦٠ ٱللَّهُ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيۡلَ لِتَسۡكُنُواْ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبۡصِرًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضۡلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشۡكُرُونَ ٦١ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡ خَٰلِقُ كُلِّ شَيۡءٖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٦٢ كَذَٰلِكَ يُؤۡفَكُ ٱلَّذِينَ كَانُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ يَجۡحَدُونَ ٦٣ ٱللَّهُ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ قَرَارٗا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءٗ وَصَوَّرَكُمۡ فَأَحۡسَنَ صُوَرَكُمۡ وَرَزَقَكُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡۖ فَتَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦٤ هُوَ ٱلۡحَيُّ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱدۡعُوهُ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَۗ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦٥

60. Ubangijinku kuma Ya ce: “Ku roƙe Ni zan amsa muku. Lalle waɗanda suke yin girman kai game da bauta min, ba da daɗewa ba za su shiga Jahannama a wulaƙance.”

61. Allah ne wanda Ya halitta muku dare don ku natsu a cikinsa, rana kuma don ku ga yadda za ku yi harka. Lalle Allah Mai falala ne ga mutane, sai dai kuma yawancinsu ba sa godewa.

62. Wannan Shi ne Allah Ubangijinku, Mahaliccin komai, babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi; to ina ne ake kautar da ku?

63. Kamar haka ne ake karkatar da waɗanda suka zamanto suna musanta ayoyin Allah.

64. Allah ne wanda Ya sanya muku ƙasa ta zama wurin zama, sama kuma ta zama rufi, Ya kuma suranta ku, sai Ya kyautata surorinku, Ya kuma arzuta ku da daɗaɗan abubuwa. Wannan fa Shi ne Allah Ubangijinku. To Allah Ubangijin talikai albarkatunsa sun yawaita.

65. Shi Rayayye ne, babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, sai ku roƙe Shi kuna masu tsantsanta addini a gare Shi. Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kiran bayinsa da su roƙe shi kuma su bauta masa shi kaɗai. Ya yi musu alƙawarin zai amsa musu addu’arsu ya kuma biya su ladan bautarsu. Ya kuma gargaɗi

masu girman kai game da roƙon sa da bauta masa, da cewa lalle a ranar alƙiyama za a jefa su Jahannama a wulaƙance, sakamakon girman kai da suka nuna.

An karɓo daga Nu'umanu ɗan Bashir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle addu'a ita ce ibada." Sannan ya karanta wannan ayar har ƙarshenta. [Ahmad #18386 da Tirmizi #3247].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ba ya roƙon Allah, to zai yi fushi da shi." [Ahmad #9719 da Tirmizi #3373 da Ibn Maja #3827].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasu ni'imominsa da manyan dalilai masu tabbatar da cancantar a bauta masa shi kaɗai, da cewa shi ne ya sanya dare ya zama duhu don mutane su nutsu su huta a cikinsa, ya sanya yini ya zama mai haske don su fita harkokinsu na rayuwa a cikinsa; ba don ya yi musu wannan ni'ima ba da tabbas sun wahala kuma da rayuwarsu ta lalace, lalle Allah mai babbar falala ne ga mutane wadda ya kewaye su da ita ta ko'ina, ciki da waje, sai dai kuma yawancin mutane ba sa gode wa wannan ni'ima da ya yi musu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa mutane cewa wanda ya yi wannan aiki fa shi ne Allah abin bautarsu mahaliccin komai, babu wani abin bauta da gaskiya sai shi kaɗai; to me ya sa mutane suke bijire wa bauta masa suna komawa ga bautar abubuwan da ba za su amfane su da komai ba?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa kamar yadda aka kautar da waɗannan mushirikan daga bautar Allah shi kaɗai, to kamar haka ne ake karkatar da duk waɗanda suka zamanto suna jayayya da ayoyin Allah, ba za su taba gane hanyar Tauhidi ba ballantana su kaɗaita Allah da bautarsu a kowane zamani a kowane wuri kuwa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana dalilan Kaɗaitakarsa waɗanda kowa yake iya gani da idonsa, inda ya bayyana cewa shi ne ya halitta wa mutane ƙasa ta zama wurin zamansu, ya kuma gina sama ta zama amintaccen rufi marar faɗowa. Shi ne kuma ya suranta mutane a cikin mahaifar iyayensu mata, ya kuma kyautata surarsu ta fi ta kowace irin halitta da ya yi, sannan ya arzuta su da kayan abinci na halal masu daɗi waɗanda za su riƙa ci suna rayuwa. Allah ya tabbatar musu da cewa, to wanda ya tanadar musu waɗannan ni'imomi manya-manya daban-daban shi ne Allah Ubangijinsu, to albarkatunsa sun yawaita, shi ne Ubangijin halittu duka babu wani abin bauta sai shi kaɗai.
Ya kuma tabbatar musu da cewa, shi rayayye ne wanda ba zai mutu ba har abada, babu wani abin bauta da gaskiya sai shi, don haka ya umarce su da su bauta masa su kuma roƙe shi shi kaɗai suna masu tsantsanta addininsu a gare shi, kada su yarda su haɗa shi da komai daga cikin halittunsa, domin shi kaɗai ne wanda yabo da godiya suka tabbata gare shi, shi ne kuma Ubangijin halittu duka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) bawan Allah ne wanda ya umarce shi ya kaɗaita shi da bauta, ya kuma guji haɗa shi da wani abu, watau kada ya yi masa shirka. Don haka shi bawan Allah ne kuma Manzonsa.

2. Girman muhimmancin tsantsanta bauta ga Allah da nisantar yi masa shirka kowace iri.

3. Kagar halitta mataki bayan mataki sunna ce ta Allah, domin mutane su yi koyi da bin abubuwa daki-daki a rayuwarsu.

4. Halittar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi ta ɗan'adam mataki bayan mataki da fito da shi duniya, tun yana jariri har ya girma ya kai munzalin ƙarfinsa, daga nan ya tsufa, har mutuwa ta riske shi. Duka waɗannan abubuwa suna faruwa ne da umarnin Allah da ƙaddarawarsa, kuma abubuwa ne da suke sanya

bawa ya ƙara yin imani ya sakankance cewa, Allah ne mai aikata komai a wannan duniya yadda ya ga dama, kuma babu wani abin bauta da gaskiya sai shi.

Suratu Ghafir (66-68)

*قُلْ إِنِّي نُهِيتُ أَنْ أَعْبُدَ ٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ لَمَّا جَآءَنِيَ ٱلْبَيِّنَٰتُ مِن رَّبِّي وَأُمِرْتُ أَنْ أُسْلِمَ لِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٦٦﴾ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَكُم مِّن تُرَابٍ ثُمَّ مِن نُّطْفَةٍ ثُمَّ مِنْ عَلَقَةٍ ثُمَّ يُخْرِجُكُمْ طِفْلًا ثُمَّ لِتَبْلُغُوٓاْ أَشُدَّكُمْ ثُمَّ لِتَكُونُواْ شُيُوخًا ۚ وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ مِن قَبْلُ ۖ وَلِتَبْلُغُوٓاْ أَجَلًا مُّسَمًّى وَلَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ﴿٦٧﴾ هُوَ ٱلَّذِي يُحْيِۦ وَيُمِيتُ ۖ فَإِذَا قَضَىٰٓ أَمْرًا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ﴿٦٨﴾

66. Ka ce: “Lalle ni an hana ni in bauta wa waɗanda kuke bauta wa ba Allah ba a yayin da (ayoyi) bayyanannu suka zo min daga Ubangijina, an kuma umarce ni da in miƙa wuya ga Ubangijin talikai.

67. “Shi ne wanda Ya halicce ku daga ƙasa, sannan daga ɗigon maniyyi, sannan daga gudan jini, daga nan Ya fito da ku kuna jarirai, sannan don ku kai ƙarfinku, sannan kuma ku zama tsofaffi. Daga cikinku kuma akwai wanda ake karɓar ransa kafin wannan; don kuma ku isa zuwa wani lokaci ƙayyadajje, don kuma ku hankalta.

68. “Shi ne wanda Yake rayawa Yake kuma kashewa; to idan zai hukunta wani al’amari sai kawai Ya ce da shi: ‘Kasance’, sai ya kasance.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya bayyana wa mushirikai hanin da ya yi masa na bautar abin da suke bauta wa ba Allah ba, saboda hujjoji bayyanannu sun zo masa masu nuna ƙacin bautar wani ba Allah ba. Ya kuma shaida musu cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya miƙa wuya gare shi ya bauta masa shi kaɗai, domin shi ne Ubangijin halittu baki ɗaya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hujjojin Kaɗaitakarsa da girman Kudurarsa, inda ya tabbatar da cewa shi ne ya halicci uban mutane gaba ɗayansu, watau Annabi Adamu, daga ƙasa, sannan ya halicci sauran ‘ya’yansa daga ɗigon maniyyi, sannan daga gudan jini, sannan bayan haka ya fito da su daga cikkunan iyayensu mata suna jarirai, sannan su yi ta girma har su kai cikar ƙarfinsu, watau ƙarfin jiki da cikar hankali, sannan su manyanta su zama tsofaffi. Daga cikinsu akwai wanda zai rasu kafin haka. Kuma Allah ya yi haka ne don ya ba su damar kaiwa zuwa wani lokaci da ya ƙayyade musu, wanda ba za su rage ba ba kuma za su ƙara ba; don kuma su hankalta su gane waɗannan hujjoji da dalilai da yake nuna musu na cikar Kudurarsa da Kaɗaitakarsa.
Hakanan ya bayyana musu cewa shi kaɗai ne mai rayawa kuma mai kashewa, duk kuma sanda ya nufi zartar da wani abu to kawai sai ya ce da shi: ‘ya kasance’ sai ko abin nan ya kasance.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nuna mamaki game da halin da masu jayayya da ƙaryata ayoyin Allah bayan sun bayyana gare su.

2. Mummunar makomar masu jayayya da ayoyin Allah don girman kai da tsaurin ido, kuma makomarsu wutar Jahannama ce wadda za su ɗanɗani azaba mai tsanani a cikinta.

3. Sukan masu farin ciki da walwala a kan aikata ƃarna da saƃon Allah.

4. Mummunan ƙarshen masu girman kai da ƙin gaskiya da mummunan sakamako da za su gamu da shi.

Suratu Ghafir (69-76)

أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ أَنَّىٰ يُصۡرَفُونَ ٦٩ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِٱلۡكِتَٰبِ وَبِمَآ أَرۡسَلۡنَا بِهِۦ رُسُلَنَاۖ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ٧٠ إِذِ ٱلۡأَغۡلَٰلُ فِيٓ أَعۡنَاقِهِمۡ وَٱلسَّلَٰسِلُ يُسۡحَبُونَ ٧١ فِي ٱلۡحَمِيمِ ثُمَّ فِي ٱلنَّارِ يُسۡجَرُونَ ٧٢ ثُمَّ قِيلَ لَهُمۡ أَيۡنَ مَا كُنتُمۡ تُشۡرِكُونَ ٧٣ مِن دُونِ ٱللَّهِۖ قَالُواْ ضَلُّواْ عَنَّا بَل لَّمۡ نَكُن نَّدۡعُواْ مِن قَبۡلُ شَيۡـٔٗاۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧٤ ذَٰلِكُم بِمَا كُنتُمۡ تَفۡرَحُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَبِمَا كُنتُمۡ تَمۡرَحُونَ ٧٥ ٱدۡخُلُوٓاْ أَبۡوَٰبَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۖ فَبِئۡسَ مَثۡوَى ٱلۡمُتَكَبِّرِينَ ٧٦

69. Ba ka ganin waɗanda suke jayayya game da ayoyin Allah, to ta yaya ake kautar da su?

70. (Su ne) waɗanda suka ƙaryata Alƙur'ani da kuma abin da Muka aiko manzanninmu da shi; to ba da daɗewa ba za su sani.

71. A yayin da ƙuƙumai suke a wuyoyinsu, da kuma sarƙoƙi ana jan su.

72. A cikin tafasasshen ruwan, sannan kuma ana ƙona su a cikin wuta.

73. Sannan kuma a ce da su: "Ina abin da kuka kasance kuna shirka da shi?

74. "Wanda ba Allah ba?" Suka ce: "Sun ɓace mana; ai ba mu kasance muna bauta wa wani abu ba a da". Kamar haka ne Allah Yake ɓatar da kafirai.

75. Wannan fa (ya same ku ne) saboda abin da kuka kasance kuna yin girman kai da shi a bayan ƙasa ba da wata hujja ba, da kuma abin da kuka kasance kuna yin walwala da shi.

76. (Za a ce da su): "Ku shiga ƙofofin Jahannama kuna masu dawwama a cikinta"; to makomar masu girman kai ta munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake nanata wa Manzonsa (ﷺ) cewa, ya dubi yadda mushirikai suke jayayya game da ayoyin Allah, har ma suna ƙaryata su duk kuwa da bayyanar gaskiya a fili. Ya yi mamakin irin wannan tsaurin kai nasu, da bijire wa gaskiya duk da cewa ta fito sarari ga kowa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffofinsu da cewa, su ne waɗanda suke ƙaryata Alƙur'ani da gaskiyar da ya aiko manzanninsa da ita. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗe su da cewa, ba da daɗewa ba za su san mummunan sakamakon ƙaryatawarsu, za su kuma ga mummunar azaba a lokacin da za a sanya musu ƙuƙumi a wuyansu a ɗaure ƙafafunsu da sarƙoƙi, mala'iku zabaniyawa suna jan su cikin tafasasshen ruwa, sannan a jefa su wuta su zama makamashinta.
A cikin irin wannan masifar azabar kuma za a riƙa yi musu tambaya ta izgili da cewa, ina ababen bautarsu da suke yi wa Allah shirka da su a duniya suka bar Allah; me ya sa ba za su zo su cece su ba? Sai kafirai su amsa da cewa, su ma ba su san inda suke ba, domin sun neme su sun rasa. Hasali ma za su dawo su ce, ai su ba su kasance suna bautar komai ba a duniya, watau su ƙaryata cewa sun bauta wa gumaka. Ko kuma suna nufin yanzu sun gane cewa abubuwan da suke bauta wa a duniya ba su cancanci bauta ba, domin ga shi sun kasa kare su daga azabar Allah. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa kamar yadda waɗannan kafiran suka ɓace, to hakanan yake ɓatar da kafirai waɗanda suka ƙi gaskiya a kowane zamani a kuma kowane wuri.
A nan ne kuma za a faɗa musu cewa, dalilin da ya sa suka tsinci kawunansu a cikin wannan mawuyacin hali shi ne, saboda farin ciki da suka riƙa nunawa a duniya da shirkar da suke yi wa Allah da kuma holewa da suka riƙa yi a kan haka.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa za a umarce su da su shiga ta ƙofofin Jahannama suna masu dawwama a cikinta har abada; to makomar masu girman kai kuwa ta yi muni.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin haƙuri da wajabcinsa a rayuwa, musamman ga masu kira zuwa ga Allah da masu ƙoƙarin kawo gyara cikin al'umma.

2. Nuna wa kafirai azabar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi musu alƙawari da ita ba a hannun Manzo (ﷺ) yake ba; wannan a hannun Allah yake, shi ne mai zartar da shi. Shi Manzo aikinsa kawai ya isar da saƙon Allah.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da wasu manzanni ban da waɗanda ambaton sunayensu ya zo a cikin Alƙur'ani, dole ne kuma mu yi imani da su a dunƙule.

Suratu Ghafir (77-78)

فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞۚ فَإِمَّا نُرِيَنَّكَ بَعۡضَ ٱلَّذِي نَعِدُهُمۡ أَوۡ نَتَوَفَّيَنَّكَ فَإِلَيۡنَا يُرۡجَعُونَ٧٧ وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا رُسُلٗا مِّن قَبۡلِكَ مِنۡهُم مَّن قَصَصۡنَا عَلَيۡكَ وَمِنۡهُم مَّن لَّمۡ نَقۡصُصۡ عَلَيۡكَۗ وَمَا كَانَ لِرَسُولٍ أَن يَأۡتِيَ بِـَٔايَةٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ فَإِذَا جَآءَ أَمۡرُ ٱللَّهِ قُضِيَ بِٱلۡحَقِّ وَخَسِرَ هُنَالِكَ ٱلۡمُبۡطِلُونَ٧٨

77. Sai ka yi haƙuri, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne. To idan Mun nuna maka sashin abin da Muke yi musu alkawari da shi na narko; ko kuma Mun karɓi ranka, to zuwa gare Mu dai za a dawo da su.

78. Haƙiƙa Mun aiko manzanni a gabaninka, daga cikinsu akwai waɗanda Muka labarta maka akwai kuma daga cikinsu waɗanda ba Mu labarta maka ba. Ba zai yiwu ba ga wani manzo ya zo da wata aya sai da izinin Allah. Sannan idan al'amarin Allah ya zo, to sai a yi hukunci da gaskiya, kuma a nan ne maɓarnata za su yi asara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da yin haƙuri game da cutarwar mutanensa da ƙaryata shi da suke yi, ya tabbatar masa cewa alƙawarin da ya yi masa na samun nasara a kansu gaskiya ne, babu kokwanto a cikinsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai nuna wa maƙiyansa azabarsa a duniya da lahira. Don haka Manzo (ﷺ) ya sanya ido ya gani, idan ya ga dama sai ya nuna masa tun a rayuwarsa wani ɓangare na azabar da ya yi musu alƙawari da ita, kamar yadda ya faru gare su a yaƙin Badar, inda aka karkashe manyansu, ko kuma idan ya karɓi ransa kafin hakan ta faru gare su, to duka dai zuwa ga Allah ne makomarsu take a ranar alƙiyama, zai kuma yi wa kowa sakayya a kan abin da ya aikata a nan duniya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Annabi (ﷺ) da cewa, ba shi ne farau ba game da wannan al'amari, domin kuwa ya aika manzanninsa masu yawa gabaninsa zuwa ga al'ummunsu, to amma sun ƙaryata su, sun kuma cutar da su, sai suka yi haƙuri a kan abin da ya same su har Allah ya kawo musu nasararsa. Daga cikin waɗannan manzanni akwai waɗanda ya ba shi labaransu; akwai kuma waɗanda bai ba shi labaransu ba.
Dangane da nacewar da kafirai suke yi wa Manzon Allah (ﷺ) a kan sai ya zo musu da wasu mu'ujizoji da suke nema, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani inda ya nuna musu cewa, zuwa da wata aya ba a hannun wani manzo yake ba; yana ga hannun Allah ne, amma shi Manzo ba (ﷺ) zai yiwu ya zo da wata aya ba sai da izinin Allah, don haka wannan dagewa tasu zalunci ne kawai. Abin da ya kamata kafirai su sani shi ne, idan wani buɗi ko hukunci ya zo tsakanin annabawa da mutanensu, to a nan Allah

yana yin hukunci ne na gaskiya da adalci, sai ya hallaka kafirai, ya tserar da muminai da manzanninsu, su kuma maɓarnata hasara ce za ta tabbata gare su saboda kafircinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yawaitar ni'imomin Allah ga bayinsa waɗanda suke wajabta musu godiya gare shi.

2. Yana daga cikin ni'imomin Allah ga ɗan'adam nuna masa ayoyi waɗanda za su sanya shi ya yi imani ya kaɗaita Allah da bautarsa.

Suratu Ghafir (79-81)
ٱللَّهُ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَنْعَٰمَ لِتَرْكَبُوا۟ مِنْهَا وَمِنْهَا تَأْكُلُونَ ﴿٧٩﴾ وَلَكُمْ فِيهَا مَنَٰفِعُ وَلِتَبْلُغُوا۟ عَلَيْهَا حَاجَةً فِى صُدُورِكُمْ وَعَلَيْهَا وَعَلَى ٱلْفُلْكِ تُحْمَلُونَ ﴿٨٠﴾ وَيُرِيكُمْ ءَايَٰتِهِۦ فَأَىَّ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ تُنكِرُونَ ﴿٨١﴾

79. Allah ne wanda Ya halitta muku dabbobin ni'ima don ku hau wasu daga cikinsu, kuma daga cikinsu kuke ci.

80. Kuna kuma da wasu abubuwan amfani game da su, don kuma ku isa (wurin) da kuke da buƙatar isa a cikin zukatanku a kansu, kuma a kansu ne da kuma a kan jiragen ruwa ake ɗaukar ku.

81. Yana kuma nuna muku ayoyinsa, to wacce (aya) ce (daga) ayoyin Allah kuke musawa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana hujjoji na Kaɗaitakarsa da girman Kudurarsa da cikar ikonsa, da cewa, shi ne wanda ya halitta wa mutane dabbobin ni'ima, watau raƙuma da shanu da tumakai da awakai, domin su hau wasu daga cikinsu kamar raƙuma, su kuma ci namansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa mutane ni'ima da abubuwan amfani daban-daban tare da waɗannan dabbobi a kowane zamani a kuma kowane wuri; ta hanyarsu ne mutane za su kai ga biyan buƙatunsu da ke cikin zukatansu, musamman tafiye-tafiye masu nisa daga gari zuwa wani gari, su kuma ɗora musu kaya masu nauyi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yana nuna wa mutane ayoyinsa masu nuna cikar Kudurarsa da kamalar ikonsa da Kaɗaitakarsa; to wace aya ce daga cikin ayoyin Allah kafirai suke musuntawa, cewa ba daga Allah suke ba? Watau idan har sun yarda da cewa, duk waɗannan ni'imomin daga Allah suke, to babu wani dalili kuma na musu da jayayya. Wajibi ne su miƙa wuya ga Allah su yarda da bautarsa shi kaɗai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yawan jama'a da tarin dukiya da tsananin ƙarfi, ba zai kare mutum daga azabar Allah ba idan har ta zo masa bai tuba ba.

2. Haɗarin yin farin ciki da ƙarya da mummunan sakamakon wanda ya yi haka.

3. Girman haɗarin da ke tattare da alfahari da amincewa da duk wani ilimi da ya ci karo da ilimin da manzannin Allah suka zo da shi, kamar ilimin da aka kafa shi a tushen kore samuwar Allah, ko kafirce wa Allah mahalicci, da ilimin tsafe-tsafe da na duba da bokanci, da duk wani ilimi da ke ɗauke da da'awar sanin gaibu.

4. Imanin kafiri ba ya inganta bayan ya ga saukar azabar Allah, wannan ba zai tserar da shi daga wannan azabar ba.

Suratu Ghafir (82-85)

أَفَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَانُوٓاْ أَكۡثَرَ مِنۡهُمۡ وَأَشَدَّ قُوَّةٗ وَءَاثَارٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ فَمَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٨٢ فَلَمَّا جَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ فَرِحُواْ بِمَا عِندَهُم مِّنَ ٱلۡعِلۡمِ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٨٣ فَلَمَّا رَأَوۡاْ بَأۡسَنَا قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَحۡدَهُۥ وَكَفَرۡنَا بِمَا كُنَّا بِهِۦ مُشۡرِكِينَ ٨٤ فَلَمۡ يَكُ يَنفَعُهُمۡ إِيمَٰنُهُمۡ لَمَّا رَأَوۡاْ بَأۡسَنَاۖ سُنَّتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي قَدۡ خَلَتۡ فِي عِبَادِهِۦۖ وَخَسِرَ هُنَالِكَ ٱلۡكَٰفِرُونَ ٨٥

82. Shin ba za su yi tafiya ba a bayan ƙasa sannan su duba yadda ƙarshen waɗanda suke gabaninsu ya zama? Sun zamanto sun fi su yawa, sun kuma fi su tsananin ƙarfi da barin gurabe a bayan ƙasa; to abin da suka kasance suna aikatawa bai wadatar musu da komai ba.

83. Sannan lokacin da manzanninsu suka zo musu da (ayoyi) bayyanannu, sai suka nuna farin ciki da ilimin da ke gare su, abin kuma da suka kasance suna yi wa izgili ya saukar musu.

84. To lokacin da suka ga azabarmu sai suka ce: “Mun yi imani da Allah Shi kaɗai, mun kuma kafirce wa abin da muka kasance muna yin shirka da shi.”

85. To imaninsu bai zamanto zai amfane su ba yayin da suka ga azabarmu; wannan sunna ce ta Allah wadda ta shuɗe a kan bayinsa. Kafirai kuma sun yi asara a nan.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana daɗa jan kunnen masu ƙaryata ayoyinsa ne don neman wani abin duniya, kamar dukiya ko matsayi ko kuma don nuna girman kai da tsaurin ido, da cewa su yi yawo a bayan ƙasa mana don su gane wa idanunsu yadda ƙarshen al’ummun da suka gabace su ya kasance bayan sun ƙaryata manzanninsu; su ga yadda Allah ya yi da su, don su ɗauki izina da wa’azi daga gare su. Waɗannan al’ummu sun fi su yawa da tarin dukiya, sun fi su ƙarfi, sun kuma fi su motsa ƙasa domin gine-gine da noma, to amma abin da suka kasance suna aikatawa bai wadatar da su da komai ba yayin da azabar Allah ta zo musu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana babban laifinsu wanda ya jawo musu azabarsa, watau lokacin da manzanninsu suka je musu da hujjoji bayyanannu sai suka bijire suka ƙaryata su, suka ƙi amincewa da su, suka ci gaba da ƙanƙame ilimin da suke tinƙaho da shi wanda ya saba wa na manzanninsu, sai azabar Allah wadda suke yi wa izgili ta saukar musu ta hallaka su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yayin da suka ga azabarsa ta tunkaro su gadan-gadan sai suka yi fargar-jaji suka gane kuskurensu, suka furta cewa, sun yi imani da Allah shi kaɗai, sun kafirce wa duk abubuwan da suke bauta wa ba Allah ba.
A ayar ƙarshe ta wannan Sura Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa imanin kafirai a wannan lokaci bayan sun ga azabar Allah ba zai yi musu wani amfani ba. Wannan kuwa sunnar Allah ce wadda ta riga ta shuɗe yake zartar da ita cikin bayinsa na cewa, imani ba zai yi amfani ba bayan azaba ta riga ta sauka. Kafirai kuwa sun yi mummunar asara da suka bari har azabar Allah ta zo musu ba su tuba sun koma gare shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da girman Alƙur’ani da bayanin kasancewarsa rahama ne ga bayi a duniya da lahira.

2. Ambatar siffofin Allah guda biyu da aka yi a nan, watau ‘Mai rahama, Mai jin ƙai’ tare da ambaton saukar da Alƙur’ani, yana nuna cewa halittu a wannan duniya kamar marasa lafiya ne kuma mayunwata suke suna buƙatar magani da abinci; Alƙur’ani kuwa ya ƙunshi duk abin da marasa lafiya suke buƙata, da abin da masu lafiya suke buƙata na abinci, don haka ya zamanto rahama ga bayin Allah.

3. Alƙur’ani Balaraben littafi ne, babu mai iya fahimtar sa sosai sai wanda ya ƙware a harshen Larabci.

4. An yi bayanin komai a Alƙur’ani dalla-dalla.

5. Alƙur’ani ya ƙunshi salo na kwaɗaitarwa da na tsoratarwa kuma tare suke tafiya kafaɗa da kafaɗa.

6. Tsananin ƙiyayyar mushirikai ga Tauhidi da masu kira zuwa gare shi a kowane zamani a kuma kowane wuri.

7. Yadda kafirai suka lalata kafofin samun shiriya da Allah ya ba su, yana nufin dogewarsu a kan ɓata da kafirci



41-Suratu Fussilat

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ta shahara da sunan *'Suratu Fussilat*' domin zuwan kalmar fussilat a ayarta ta uku.
A wasu littafan tafsiri an kira ta da sunan '*Suratu As-Sajda*' ko kuma '*Ha mim As-Sajda*' kamar yadda Al-Imamul Bukhari ya kira ta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Maganar malamai ta zo ɗaya a kan cewa sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta sittin da ɗaya (61) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan 'Suratu *Ghafir*' kafin '*Suratu Zukhruf*'.

4. Adadin ayoyinta:
Ayoyinta hamsin da huɗu ne (54) a lissafin mutanen Kufa. A wurin mutanen Madina da Makka kuwa adadinsu hamsin da uku ne (53). A wurin mutanen Sham da Basra kuwa hamsin da biyu ne (52).

5. Babban Jigonta:
Surar tana bayani ne a kan tabbatar da Kaɗaitakar Allah, da gaskiyar ranar alƙiyama, da tabbatar da manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ) da Alƙur'ani da ya zo da shi, tare da bayanin yadda ya kamata a kirawo waɗanda suka bijire wa gaskiya da kuma siffofin mai kira zuwa ga Allah.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Bayanin girman Alƙur'ani da zamantowarsa shiriya kuma mu'ujiza wanda ƙarya ba za ta shiga cikinsa ba.
• Rushe soke-soken mushirikai game da Alƙur'ani da nuna musu cewa ya sauka da harshensu na Larabci, don haka bai dace su kasa fahimtar sa ko amfana da shi ba.
• Tsawatar wa mushirikai game da kafirce wa Allah da suke yi duk da cewa, shi ne mahaliccin sammai da ƙasa da abin da suka ƙunsa na hujjoji masu tabbatar da Kaɗaitakarsa.
• Yi musu gargaɗi ta hanyar tunatar da su labaran al'ummun da suka gabata waɗanda suka ƙaryata manzannin Allah, Allah ya hallaka su.
• Tsoratar da su azabar lahira lokacin da jinsu da ganinsu za su ba da shaida a kansu.
• Gargaɗin su game da shaiɗanun mutane da aljannu waɗanda za su ƙawata musu kafirci su kuma su bi su a kai, da sanar da su cewa ranar alƙiyama za su yi nadamar biyayyar da suka yi musu.
• Bayanin karramawar da Allah zai yi wa muminai.
• Umartar Manzon (ﷺ) Allah da ya kawar da cutarwarsu ta hanya mafi kyau, ya kuma yi haƙuri a kan cin mutuncinsa da kafirai suke yi, sannan ya riƙa neman tsari da Allah daga sharrin Shaiɗan.
• Ambaton hujjojin da suke tabbatar da Kaɗaitakar Allah da cikar Kudurarsa, watau halittar rana da wata da sauran manya-manyan halittunsa.

• Tabbatar da yiwuwar tashi bayan mutuwa, a wani lokaci da Allah ne kaɗai ya san ranar zuwansa.
• Karfafa gwiwar Annabi (ﷺ) da muminai da yi musu bayanin yadda mala'iku suke sauko da wahayi da bushara a gare su.

Suratu Fussilat (1-5)
حمٓ ۝١ تَنزِيلٌ مِّنَ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ۝٢ كِتَٰبٞ فُصِّلَتۡ ءَايَٰتُهُۥ قُرۡءَانًا عَرَبِيّٗا لِّقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ۝٣ بَشِيرٗا وَنَذِيرٗا فَأَعۡرَضَ أَكۡثَرُهُمۡ فَهُمۡ لَا يَسۡمَعُونَ ۝٤ وَقَالُواْ قُلُوبُنَا فِيٓ أَكِنَّةٖ مِّمَّا تَدۡعُونَآ إِلَيۡهِ وَفِيٓ ءَاذَانِنَا وَقۡرٞ وَمِنۢ بَيۡنِنَا وَبَيۡنِكَ حِجَابٞ فَٱعۡمَلۡ إِنَّنَا عَٰمِلُونَ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. HA MIM.

2. (Alƙur'ani) saukakke ne daga (Allah) Mai rahama, Mai jin ƙai.

3. (Shi) Littafi ne Alƙur'ani Balarabe da aka rarrabe ayoyinsa ga mutanen da suke sanin (ma'anarsa).

4. Mai albishir ne kuma mai gargaɗi, sai yawancinsu suka bijire, don haka su ba sa jin (kira).

5. Suka kuma ce: "Zukatanmu suna cikin rufi game da abin da kuke kiran mu zuwa gare shi; a cikin kunnuwanmu kuma akwai nauyi, kuma tsakaninmu da kai akwai shamaki, sai ka yi aiki da (addininka), lalle mu ma masu yin aiki ne (da namu)."
An buɗe wannan Sura da wasu haruffa, kamar yadda aka buɗe wasu surori a baya. [Dubi tafsirinmu na farkon *Suratul Baƙara* domin ƙarin bayani].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana matsayin Alƙur'ani da cewa shi saukakken littafi ne daga Allah wanda rahamarsa ta yalwaci kowa da komai a nan duniya, mai kuma keɓantacciyar rahama ga muminai a lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffar Alƙur'ani da cewa shi littafi ne da aka yi bayanin ayoyinsa daki-daki ta yadda kowa zai iya fahimta bakin gwargwado, sannan ya sanya shi Balaraben littafi ga mutanen da suke sanin ma'anoninsa suke amfana da shi da abin da ya ƙunsa na shiriya.
Sannan Allah ya nuna cewa Alƙur'ani mai yi wa muminai albishir ne da gwaggwaɓan sakamako da Allah ya tanadar musu, kuma mai gargaɗi ne ga kafirai game da azaba mai raɗaɗi idan ba su tuba zuwa ga Allah ba. To amma sai mafi yawancinsu suka bijire wa sauraron shiriyar da yake kiran su zuwa gare ta, suka daina sauraron sa sauraro na karɓa da miƙa wuya.
Har ma kafiran suna cewa zukatansu a rufe suke ruf, ba za su taɓa fahimtar wa'azin da ake yi musu ba, kuma akwai kurumta tare da kunnuwansu, don haka ba sa jin duk wani kira da ake yi musu. Hasali ma tsakaninsu da Manzon Allah (ﷺ) da yake kiran su akwai shamaki da yake hana muryarsa isa zuwa inda suke, saboda haka suna sanar da shi cewa ya je ya yi aiki da fahimtarsa a kan hanyar da ya zaɓa, su ma za su yi aiki ne da fahimtarsu a kan hanyar da suka zaɓa wa kawunansu, su kam ba za su bi shi ba.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wata rana Kuraishawa sun yi taro, sai suka ba wa junansu shawara a kan su duba a cikinsu su zaɓi wanda ya fi kowa sanin sihiri da waƙa da bokanci don ya je ya sami Annabi (ﷺ) wanda suke zargin sa da ya zo ne don ya rarraba kawunansu, ya tarwatsa musu al'amuransu ya kuma kushe musu addininsu. Ya tattauna da shi ya ga wace amsa zai ba shi. Sai suka zaɓi Utbatu ɗan Rabi'atu domin suna ganin babu wanda ya fi shi dacewa da wannan aiki. Sai ya tafi ya haɗu da Manzon Allah (ﷺ) ya tambaye shi cewa: "Kai Muhammadu, da kai da Abdullahi wane ne ya fi?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi masa shiru bai ce masa komai ba. Sai ya sake tambayar sa cewa: "To kai

da Abdulmuɗɗalibi wane ne ya fi?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi masa shiru. Sai Utbatu ya ce: “Idan har ka yarda cewa waɗannan mutanen biyu sun fi ka, to su, sun bauta wa allolin da kake kushewa. Idan kuma kana ganin kai ka fi su, to sai ka faɗa mu ji. Mu dai Wallahi ba mu taɓa ganin ɗan da ya zame wa mutanensa alaƙaƙai ba kamarka. Ka rarraba kawunanmu, ka tarwatsa mana al’amarinmu, ka kushe addininmu, ka kuma kunyata mu a cikin ‘yan’uwanmu Larabawa; har labari ya bazu a cikinsu cewa an sami matsafi a cikin Kuraishawa, an kuma sami boka a cikinsu. Wallahi babu abin da ya rage mana sai dai kawai mu ji ihu irin na mace mai ciki, daga nan kuma kowa ya zare takobinsa mu yi ta sarar junanmu har sai mun ƙarar da kanmu. Kai wannan mutum, ka faɗa mana, idan buƙatar dukiya ce kake yi sai mu tara maka dukiya har sai ka fi kowa kuɗi cikin Kuraishawa. Idan kuma aure kake buƙata, to ka zaɓi matan Kuraishawan da suka yi maka, mu za mu aura maka guda goma.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: “Ka gama maganarka?” Sai ya ce: “Na’am.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi Bismilla ya fara karanto farkon wannan Sura har sai da ya kai aya ta 13, sai Utbatu ya ce: “Ya isa hakanan, ya isa hakanan. Ban da wannan ba ka da wata maganar?” Annabi ya ce masa: “Babu.” Sai ya koma wajen Kuraishawa, suka tambaye shi: “Mene ne labari?” Sai ya ce: “Babu abin da na bari wanda nake ganin za ku faɗa masa shi har sai da na faɗa masa.” Sai suka ce: “To ya ba ka amsa?” Sai ya ce: “A’a, na rantse da wanda ya kafa ginin Ka’aba, ban fahimci komai daga maganarsa ba sai dai kawai na ji yana muku gargaɗi da tsawa irin tsawar Adawa da Samudawa.” Sai suka ce: “Kaiconka, mutum yana yi maka magana da harshen Larabci amma ka ce ba ka fahimci komai daga maganarsa ba?” Ya ce: “E, Wallahi ba abin da na fahimta sai maganar tsawar nan kaɗai.” [Abdu bin Humaid #1119 da Ibn Abi Shaiba, *Al-Musannaf* #36560 da Abu Ya’ala #1818 da Al-Hakim #3002].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cewa Annabi (ﷺ) mutum ne kamar sauran mutane, sai dai Allah ya ɗaukaka darajarsa a kan kowa, domin shi ana yi masa wahayi.

2. Wajabcin tsayawa kyam a kan shari’ar Allah ba tare da karkace mata ba.

3. Faɗakarwa a kan ikhlasi, watau ya wajaba duk wani mai aiki ya zamanto Allah ne kaɗai manufarsa da shi, kuma yana aiki ne domin samun yardarsa da sakamakonsa, watau gidan Aljanna.

4. Duk yadda bawa ya so ya tsaya ɗoɗar a kan hanyar Allah sai an same shi da kasawa a wani lokaci, don haka yake buƙatar neman gafarar Allah koyaushe.

5. Wajabcin ba da zakkar dukiya da kuma tsarkake zukata daga duk wata ƙazanta.

6. Duk mumini zai sami jin daɗi na har abada a ranar alƙiyama.

Suratu Fussilat (6-8)
قُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞ فَٱسۡتَقِيمُوٓاْ إِلَيۡهِ وَٱسۡتَغۡفِرُوهُۗ وَوَيۡلٞ لِّلۡمُشۡرِكِينَ ٦ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُم بِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ كَٰفِرُونَ ٧ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونٖ ٨

6. Ka ce: “Ni ba wani ba ne sai mutum kamarku, ana yiwo min wahayin cewa, abin bautarku abin bauta ne Guda Ɗaya, sai ku miƙe kyam zuwa gare Shi, kuma ku nemi gafararsa. Tsananin azaba kuma ya tabbata ga mushirikai.

7. “Waɗanda ba sa ba da zakka, kuma su masu kafircewa ne da (ranar) lahira.”

8. Lalle waɗanda suka yi imani kuma suka yi aiki nagari suna da lada marar yankewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya faɗa wa mushirikai masu jayayya da shi a kan manzancinsa da Alƙur'ani cewa shi fa kawai mutum ne kamarsu mai ƙirar jiki da kamanni irin nasu, watau shi ba mala'ika ba ne ba kuma aljani ne ba, bambancinsu shi ne, shi ana yi masa wahayi da cewa abin bautarsu na gaskiya Ɗaya ne shi ne Allah, don haka su kama hanyar da za ta sada su da shi, su nemi gafarar zunubansu daga gare shi. Kuma su sani cewa azaba da hallaka sun tabbata ga mushirikai masu ɓauta wa wasu tare da Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta mushirikai da cewa su ne waɗanda ba sa bayar da zakkar dukiyoyinsu kuma suna kafirce wa ranar lahira da abin da ta ƙunsa na ni'imominta da azabarta.
Sai kuma ya ambaci sakamakon waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa suka yi kuma ayyuka nagari da cewa suna da sakamakon da ba ya yankewa, watau Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu abin mamaki kamar na waɗanda za su kafirce wa Allah, su riƙa bauta wa wasu abubuwa ba shi ba, alhalin shi ne ya kaɗaita da halittar sammai da ƙasa da duk abin da idanunsu suke gani da wanda ba sa gani.

2. Duk manya-manyan halittun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sun miƙa wuya gare shi ba tare da gardama ba in ban da mutum da aljan kaɗai.

3. Kwanakin yin halittar sammai da ƙasa, watau kwana shida, sun fara ne daga Lahadi an kammala su a ranar Juma'a. Allah yana iya halittar dukkan komai da kalma ɗaya tak, watau '*kun',* to amma ya zaɓi ya yi waɗannan halittu a cikin kwana shida domin ya koyar da bayinsa sunnar bin komai daki-daki cikin nutsuwa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara abincin duk halittunsa a cikin ƙasa tun lokacin da ya halicce ta, don haka babu dalilin nuna damuwa da cewa abinci zai yi ƙaranci a duniya saboda yawan hayayyafa da ƙaruwa da ɗan'adam yake ta yi, kamar yadda ƙungiyoyin ƙasashen duniya suke kuzuzutawa, irin Hukumar Samar da Abinci da Kula da Noma ta Masajilisar Dinkin Duniya, watau *Food and Agriculture Organization* (FAO). Suna yin haka ne kuwa domin tabbatar da manufarsu ta rage ƙaruwar adadin al'ummar Musulmi a duniya.

5. Yana daga cikin hikimar halittar taurari a sama zamantowarsu tamkar fitilu masu haskakawa, su ƙawata ta su kuma zama tsaro daga shaiɗanu masu zuwa satar sauraron maganganun mala'iku.

Suratu Fussilat (9-12)
۞قُلۡ أَئِنَّكُمۡ لَتَكۡفُرُونَ بِٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡأَرۡضَ فِي يَوۡمَيۡنِ وَتَجۡعَلُونَ لَهُۥٓ أَندَادٗاۚ ذَٰلِكَ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٩ وَجَعَلَ فِيهَا رَوَٰسِيَ مِن فَوۡقِهَا وَبَٰرَكَ فِيهَا وَقَدَّرَ فِيهَآ أَقۡوَٰتَهَا فِيٓ أَرۡبَعَةِ أَيَّامٖ سَوَآءٗ لِّلسَّآئِلِينَ ١٠ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰٓ إِلَى ٱلسَّمَآءِ وَهِيَ دُخَانٞ فَقَالَ لَهَا وَلِلۡأَرۡضِ ٱئۡتِيَا طَوۡعًا أَوۡ كَرۡهٗا قَالَتَآ أَتَيۡنَا طَآئِعِينَ ١١ فَقَضَىٰهُنَّ سَبۡعَ سَمَٰوَاتٖ فِي يَوۡمَيۡنِ وَأَوۡحَىٰ فِي كُلِّ سَمَآءٍ أَمۡرَهَاۚ وَزَيَّنَّا ٱلسَّمَآءَ ٱلدُّنۡيَا بِمَصَٰبِيحَ وَحِفۡظٗاۚ ذَٰلِكَ تَقۡدِيرُ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡعَلِيمِ ١٢

9. Ka ce: "Yanzu kwa riƙa kafircewa da wanda Ya halicci ƙasa a cikin (gwargwadon) kwana biyu, kuna kuma sanya masa kishiyoyi? Wannan fa Shi ne Ubangijin talikai!

10. “Ya kuma sanya kafaffun duwatsu a cikinta daga samanta, Ya kuma yi albarka a cikinta, Ya kuma ƙaddara dangogin abincinta a cikin kwana huɗu (tare da kwanaki biyu na halittar ƙasa) daidai da daidai ga masu tambaya.

11. “Sannan Ya nufi zuwa sama, (a sannan) ita kuma hayaƙi ce, sai Ya ce da ita da kuma ƙasa: “Ku zo cikin biyayya ko kuma bisa tilas.” Suka ce: ‘Mun zo muna masu biyayya’.

12. “Sai Ya mayar da su sammai bakwai a cikin kwana biyu, Ya kuma yi wa kowacce sama wahayin umarninta. Muka kuma ƙawata saman duniya da taurari da kuma tsaro. Wannan tsari ne na Allah Mabuwayi, Masani.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikar Kudurarsa da hikimarsa wadda ke tabbatar da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da abokin tarayya ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya ƙalubalanci mushirikai da cewa, me ya sa suke kafirce wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda ya halicci ƙasa a cikin kwana biyu, watau ranar Lahadi da ranar Litinin, suke kuma sanya masa kishiyoyi suna bauta musu tare da shi? Wannan fa shi ne Ubangijin talikai gaba ɗayansu. Kuma shi ne wanda ya kakkafa duwatsu a cikin ƙasa domin su riƙe ta su hana ta yin tangal-tangal. Sannan ya ƙaddara samuwar abincin mutane da na dabbobi iri-iri a cikinta cikin kwana huɗu, watau haɗe da kwanakin halittar ƙasa guda biyu, su ne ranar Talata da Laraba, kwanaki huɗu cikakku don masu yin tambayar son sanin yadda al’amarin ya faru.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nufi halittar sama, ita kuma a lokacin hayaƙi ce, sai ya umarce ta ita da ƙasa cewa su zo suna masu miƙa wuya a bisa zaɓinsu ko kuma ala tilas, sai suka amsa masa da cewa za su zo a bisa zaɓin kansu, domin ba su da wani zaɓi bayan nasa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya cika halittar sammai bakwai a cikin kwana biyu, watau Alhamis da Juma’a, cikon kwana shida kenan na halittar sammai da ƙasa. Daga nan sai Allah ya yi wa kowace sama wahayin abin da ya ƙaddara samuwarsa a cikinta, da abin da ya yi umarni da shi na ɗa’a da bautarsa. Sai ya bayyana cewa ya sanya taurari a sama ta duniya domin su zama ado da kuma tsaro a gare ta daga shaiɗanu masu zuwa satar sauraro. Duk waɗannan abubuwa da aka ambata wani tsari ne na Allah mabuwayi wanda babu mai iya ja da shi, masanin komai da ke cikin halittunsa na sama da na ƙasa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi da tsoratarwa game da bijire wa gaskiya da kafewa a kan kafirci da saɓon Allah.

2. Tabbatar da cewa da’awar dukkan annabawa ta haɗu ne a kan Tauhidi da guje wa shirka.

3. Hujjar kafirai da ta sa su kafirce wa manzanninsu, ita ce kasancewar manzannin mutane ne ba mala’iku ba, su a ganinsu ba mutane irinsu ya kamata Allah ya aiko musu ba, sai dai mala’iku.

4. Girman kai da alfahari da ƙarfi kowanne iri ne su suke hana wasu mutane karɓar gaskiya.

5. Duk yadda azaba ta tsananta ga kafiri a duniya, to azabar lahira ta fi ta tsanani da wulaƙanci.

6. Babu wani sauran zaɓi ga mutumin da ya yi watsi da shiriyar Allah sai makantar basira, watau kafirci da saɓon Allah.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana saukar wa da bayinsa azaba ne sakamakon laifukansu.

8. Imani da takawa su ne kaɗai hanyar samun kuɓuta daga azabar Allah a duniya da lahira.

Suratu Fussilat (13-18)
فَإِنۡ أَعۡرَضُواْ فَقُلۡ أَنذَرۡتُكُمۡ صَٰعِقَةٗ مِّثۡلَ صَٰعِقَةِ عَادٖ وَثَمُودَ ١٣ إِذۡ جَآءَتۡهُمُ ٱلرُّسُلُ مِنۢ بَيۡنِ أَيۡدِيهِمۡ وَمِنۡ خَلۡفِهِمۡ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّا ٱللَّهَۖ قَالُواْ لَوۡ شَآءَ رَبُّنَا لَأَنزَلَ مَلَٰٓئِكَةٗ فَإِنَّا بِمَآ أُرۡسِلۡتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ١٤ فَأَمَّا عَادٞ فَٱسۡتَكۡبَرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَقَالُواْ مَنۡ أَشَدُّ مِنَّا قُوَّةًۖ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّ ٱللَّهَ ٱلَّذِي خَلَقَهُمۡ هُوَ أَشَدُّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗۖ وَكَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجۡحَدُونَ ١٥ فَأَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ رِيحٗا صَرۡصَرٗا فِيٓ أَيَّامٖ نَّحِسَاتٖ لِّنُذِيقَهُمۡ عَذَابَ ٱلۡخِزۡيِ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَعَذَابُ ٱلۡأٓخِرَةِ أَخۡزَىٰۖ وَهُمۡ لَا يُنصَرُونَ ١٦ وَأَمَّا ثَمُودُ فَهَدَيۡنَٰهُمۡ فَٱسۡتَحَبُّواْ ٱلۡعَمَىٰ عَلَى ٱلۡهُدَىٰ فَأَخَذَتۡهُمۡ صَٰعِقَةُ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡهُونِ بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ١٧ وَنَجَّيۡنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ١٨

13. To idan suka bijire sai ka ce: “Na tsoratar da ku da tsawa irin tsawar Adawa da Samudawa.

14. “Lokacin da manzanninsu suka zo musu ta gabansu da ta bayansu cewa: ‘Kada ku bauta wa komai sai Allah.’” Suka ce: “Da Ubangijinmu Ya ga dama, da Ya saukar da mala’iku, saboda haka mu lalle masu kafirce wa abin da aka aiko ku da shi ne.’”

15. Amma Adawa sai suka yi girman kai a bayan ƙasa ba a kan gaskiya ba, suka kuma ce: “Wane ne ya fi mu tsananin ƙarfi?” Yanzu ba su ga cewa lalle Allah wanda Ya halicce su Ya fi su tsananin ƙarfi ba? Sun kuma kasance suna musanta ayoyinmu.

16. Sai Muka aiko musu da wata iska mai ƙara a wasu kwanaki masu cike da shu’umci don Mu ɗanɗana musu azabar kunyata a rayuwar duniya; azabar lahira kuma ta fi kunyatarwa; alhalin su ba za a taimake su ba.

17. Amma Samudawa kuma sai Muka nuna musu hanyar shiriya, sai suka zaɓi ɓata a kan shiriya, sai tsawar azabar wulaƙanci ta kama su saboda abin da suka kasance suna tsuwurwuta.

18. Muka kuma tserar da waɗanda suka yi imani suka kuma kasance masu kiyaye dokokin Allah.

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar Annabi (ﷺ) da ya gargaɗi mutanensa mushirikai cewa idan suka bijire suka ƙi yin imani da Kaɗaitakar Allah da manzancin Annabi (ﷺ), to yana tsoratar da su da wata azaba da za ta saukar musu, irin azabar da ta sauka a kan Adawa da Samudawa yayin da suka ƙaryata manzanninsu.
Lokacin da manzanni suka dinga zuwa musu ɗaya bayan ɗaya suna umartar su da abu guda ɗaya, shi ne su bauta wa Allah shi kaɗai kada su haɗa komai da shi, to amma maimakon su yi imani sai suka riƙa cewa, ai bai kamata a ce mutane irinsu ne Allah zai aiko a matsayin manzanni ba; da ya ga damar aiko da manzanni to ai sai ya saukar da mala’iku daga sama su riƙa yi musu wa’azi. Don haka suka tabbatar musu cewa su sun kafirce wa duk abin da aka aiko su da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin kafircin Adawa da na Samudawa da irin azabar da ya saukar musu, da cewa su Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) baya ga kafircinsu, su mutane ne da suka nuna girman kai a bayan ƙasa ba a kan gaskiya ba, suka zalunci waɗanda suke tare da su, suna kuma alfahari da ƙarfin da aka ba su, har suna cewa wane ne ya fi su tsananin ƙarfi? Watau suna ganin cewa babu wanda ya fi ƙarfinsu; wannan ne ya ruɗe su har suka riƙa aikata abin da suka ga dama a bayan ƙasa. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa, shin ba su san cewa Allah wanda ya halicce su ya ba su wannan ƙarfin da suke taƙama da shi ya fi su tsananin ƙarfi ba?

Ba don ya halicce su ba da babu su, da a ce sun yi tunani a kan haka, da ba za su yi ɗagawar da suka yi ba, amma sai suka musunta ayoyin Allah waɗanda Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo musu da su suka ƙaryata shi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa sakamakon kafircinsu ya sa ya aiko musu da wata iska mai tsananin ƙara a cikin wasu shu'uman kwanaki mara sa alheri saboda tsananin azabar da ke cikinsu, don ya ɗanɗana musu azabar wulaƙanci da ƙasƙanci a rayuwar duniya, kuma azabar lahira wadda take jiran su ta fi tsananin ƙasƙanci da wulaƙanci, ga shi kuma a lahira babu wanda zai taimaka musu ya kuɓutar da su daga wannan azabar.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, su kuma Samudawa mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya bayyana musu hanyar shiriya amma sai suka fifita ɓata a kan shiriya, sai azabar tsawa mai wulaƙantarwa ta faɗa musu, saboda kafirci da saɓon Allah da suka riƙa aikatawa.
Allah kuma (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da muminai waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa suka kuma yi taƙawa, watau bin umarnin Allah da guje wa haninsa, ya kuɓutar da su daga azaba mai raɗaɗi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mummunan yanayi da kafirai za su tsinci kawunansu a cikinsa ranar alƙiyama shi ne lokacin da za a kora su zuwa wutar Jahannama.

2. Gaɓoɓi za su yi wa masu su shaida a ranar alƙiyama, kamar yadda ya zo a cikin *Suratu Yasin* aya ta 65. [Dubi hadisin da muka ambata a can].

3. Mummunan zato ne ga Allah mutum ya riƙa tsammanin cewa, Allah bai san abin da yake aikatawa na kafirci da saɓonsa ba. Kuma wannan zato shi ne musabbabin hallakar bawa da taɓewarsa ranar alƙiyama.

4. Babu yadda wani zai iya haƙuri da azabar wuta ta duniya ballantana kuma wutar lahira wadda zafinta ya ninninka zafin ta duniya sau saba'in.

Suratu Fussilat (19-24)
وَيَوۡمَ يُحۡشَرُ أَعۡدَآءُ ٱللَّهِ إِلَى ٱلنَّارِ فَهُمۡ يُوزَعُونَ ١٩ حَتَّىٰٓ إِذَا مَا جَآءُوهَا شَهِدَ عَلَيۡهِمۡ سَمۡعُهُمۡ وَأَبۡصَٰرُهُمۡ وَجُلُودُهُم بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٢٠ وَقَالُواْ لِجُلُودِهِمۡ لِمَ شَهِدتُّمۡ عَلَيۡنَاۖ قَالُوٓاْ أَنطَقَنَا ٱللَّهُ ٱلَّذِيٓ أَنطَقَ كُلَّ شَيۡءٖ وَهُوَ خَلَقَكُمۡ أَوَّلَ مَرَّةٖ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٢١ وَمَا كُنتُمۡ تَسۡتَتِرُونَ أَن يَشۡهَدَ عَلَيۡكُمۡ سَمۡعُكُمۡ وَلَآ أَبۡصَٰرُكُمۡ وَلَا جُلُودُكُمۡ وَلَٰكِن ظَنَنتُمۡ أَنَّ ٱللَّهَ لَا يَعۡلَمُ كَثِيرٗا مِّمَّا تَعۡمَلُونَ ٢٢ وَذَٰلِكُمۡ ظَنُّكُمُ ٱلَّذِي ظَنَنتُم بِرَبِّكُمۡ أَرۡدَىٰكُمۡ فَأَصۡبَحۡتُم مِّنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٢٣ فَإِن يَصۡبِرُواْ فَٱلنَّارُ مَثۡوٗى لَّهُمۡۖ وَإِن يَسۡتَعۡتِبُواْ فَمَا هُم مِّنَ ٱلۡمُعۡتَبِينَ ٢٤

19. (Ka tuna) kuma ranar da za a tara maƙiya Allah zuwa wuta ana kuma kora su.

20. Har sai lokacin da suka zo mata, jinsu da ganinsu da fatunsu za su ba da shaida a kan abin da suka kasance suna aikatawa.

21. Sai Suka ce da fatunsu: "Don me kuka ba da shaida a kanmu?" Suka ce: "Allah da Ya bai wa kowane abu ikon yin furuci mu ma Shi Ya ba mu ikon furuci, Shi ne kuma Ya halicce ku tun farko, gare Shi kuma kaɗai za a mayar da ku."

22. Kuma ba ku kasance kuna ɓoye (ayyukanku) ba, don gudun kada jinku da ganinku da fatunku su ba da shaida a kanku ba, sai dai kuna tsammanin cewa Allah ba Ya sane da yawancin abin da kuke aikatawa.

23. Wannan kuma shi ne zatonku da kuka yi ga Ubangijinku da ya hallakar da ku, sai kuka wayi gari cikin hasararru.

24. To idan ma sun yi haƙuri wuta ce dai makomarsu; idan kuma suka nemi kawo wani hanzari, to su ba sa cikin waɗanda za a karɓi hanzarinsu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda zai azabtar da maƙiyansa a ranar alƙiyama, lokacin da za a tattara su a haɗa na farko da na ƙarshensu a gargaɗa su da ƙarfi zuwa wutar Jahannama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yayin da za su iso wannan wutar sai su dinga musunta laifukan da suka yi a duniya, daga nan sai jinsu da ganinsu da fatunsu su ba da shaida game da abin da suka kasance suna aikatawa na kafirci da saɓon Allah, watau kowace gaɓa za ta furta irin saɓon Allah da ta aikata da lokaci da kuma wurin da ta aikata shi.
To daga nan fa kafirai ba su da ikon ci gaba da musu, sai su fara zargin gaɓoɓinsu a kan irin wannan shaida da suka bayar a kansu, har ma su ce da fatun nasu, me ya sa za su ba da irin wannan mummunar shaida a kansu? Sai fatun su amsa musu da martanin cewa, Allah wanda ya ba wa kowane abu ikon yin furuci su ma shi ne ya ba su wannan ikon, suka kuma nuna musu cewa kada su manta fa shi ne ya halicce su tun a karon farko, don haka babu abin da zai gagare shi, kuma zuwa gare shi shi kaɗai za a mayar da su domin ya yi musu hisabi a kan ayyukansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa za a shaida musu cewa, ai da man tun a duniya ba sa ɓoye wani aiki na kafirci da saɓon Allah da suke yi don gudun kada jinsu da ganinsu da fatunsu su ba da shaida a kansu; suna fitowa ne gaba-gaɗi su aikata ayyukan da suka ga dama a sarari, domin ba su yi imani da ranar hisabi ko uƙuba ko sakamako na bayan mutuwa ba, kuma suna tsammanin Allah ba ya sanin yawancin abin da suke aikatawa. Wannan mummunan zato nasu shi ne ya ruɗe su har suka ci gaba da aika-aikarsu ba tare da sun tuba ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa wannan mummunan zaton da suka yi wa Ubangijinsu shi ne ya hallaka su har suka wayi gari suna cikin hasararru waɗanda suka yi hasarar duniya da lahira.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa azabarsa ta riga ta tabbata a kansu, don haka ko su yi haƙuri da shaidar da gaɓoɓinsu suka bayar a kansu ko ba su yi haƙuri ba duka ɗaya ne, domin wuta ce makomarsu, idan kuma suka nemi Allah ya ɗauke musu azaba ya yafe musu laifukansu, to su sani cewa sun makara, ba za su taɓa samun afuwarsa ba ballantana har ya yafe musu su sami shiga Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirci da saɓon Allah su ne suke ba wa shaiɗanu galaba a kan ɗan'adam.

2. Idan maɓarnata suka kasa fuskantar hujja da hujja sai su koma ga hayaniya da hargowa, domin su hana mutane sauraron gaskiya, saboda gaskiya tana da tasiri a kan zukata, kuma nan da nan take kama lafiyayyen hankali.

3. Mabiya za su yi fatan shugabanninsu na ɓata su haɗu da mafi tsananin azaba a ranar alƙiyama, domin su huce haushinsu na ɓatar da su da suka yi.

4. Wuta hawa-hawa ce, wasu ‘yan wuta sun fi wasu zamantowa can ƙasanta.

Suratu Fussilat (25-29)

*وَقَيَّضۡنَا لَهُمۡ قُرَنَآءَ فَزَيَّنُواْ لَهُم مَّا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡ وَحَقَّ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقَوۡلُ فِيٓ أُمَمٖ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِم مِّنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ خَٰسِرِينَ٢٥ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَا تَسۡمَعُواْ لِهَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ وَٱلۡغَوۡاْ فِيهِ لَعَلَّكُمۡ تَغۡلِبُونَ٢٦ فَلَنُذِيقَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ عَذَابٗا شَدِيدٗا وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَسۡوَأَ ٱلَّذِي كَانُواْ يَعۡمَلُونَ٢٧ ذَٰلِكَ جَزَآءُ أَعۡدَآءِ ٱللَّهِ ٱلنَّارُۖ لَهُمۡ فِيهَا دَارُ ٱلۡخُلۡدِ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجۡحَدُونَ٢٨ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ رَبَّنَآ أَرِنَا ٱلَّذَيۡنِ أَضَلَّانَا مِنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِ نَجۡعَلۡهُمَا تَحۡتَ أَقۡدَامِنَا لِيَكُونَا مِنَ ٱلۡأَسۡفَلِينَ٢٩

25. Muka kuma haɗa su da abokai (shaiɗanu), sai suka ƙawata musu abin da yake gabansu (na duniya) da abin da yake bayansu (na musun alƙiyama), sai kalmar (azaba) ta tabbata a kansu (na zamantowa) cikin al'ummun da suka gabace su na aljannu da mutane; lalle su, sun kasance hasararru.

26. Waɗanda kuma suka kafirta suka ce: "Kada ku saurari wannan Alƙur'ani, ku riƙa yin hayaniya a cikinsa don ku yi rinjaye."

27. To tabbas za Mu ɗanɗana wa waɗanda suka kafirta azaba mai tsanani, kuma tabbas za mu saka musu da mafi munin abin da suka kasance suna aikatawa.

28. Wannan fa shi ne sakamakon maƙiya Allah (watau) wuta; suna da gidan dawwama a cikinta; sakamako ne saboda abin da suka kasance suna musuntawa na ayoyinmu.

29. Waɗanda kuma suka kafirta suka ce: "Ya Ubangijinmu, Ka nuna mana waɗanda suka ɓatar da mu daga aljannu da mutane, mu sanya su a ƙarƙashin dugaduganmu don su zamanto cikin na can ƙasan ƙasa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya haɗa kafirai da wasu abokai shaiɗanu da koyaushe suke tare da su suna ƙawata musu kafirci da saɓon Allah a duniya, suna mantar da su ranar lahira suna kuma hana su yi mata kyakkyawan tanadi ko ma su sanya su ƙaryata ta, har lokacin da kalmar azaba ta tabbata a kansu su zamanto cikin sauran al'ummun da suka shuɗe gabaninsu na aljannu da mutane. Lalle dukkansu sun kasance hasararru, domin za su yi hasarar kawunansu da iyalansu a ranar alƙiyama, saboda wuta ce makomarsu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafiran Ƙuraishawa suka riƙa yaƙar Alƙur'ani suna hana mutane sauraron karatunsa suna faɗa musu cewa, kada su saurare shi kuma duk sanda suka ji ana karanta shi to su yi ta hayaniya da hargowa a wurin don kada mutane su sami damar jin abin da ake karantawa, domin suna zaton ta haka ne za su yi galaba su kawo ƙarshen da'awa zuwa ga Allah, su huta da jin karatun Alƙur'ani.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, lalle sai ya ɗanɗana matsananciyar azabarsa a ranar alƙiyama ga waɗanda suka kafirce masa suka ƙaryata manzanninsa, kuma tabbas sai ya saka musu da mafi munin abin da suka kasance suna aikatawa na kafirci da saɓonsa.
Wannan azabar kuma da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambata ita ce sakamakon maƙiya Allah masu ƙaryata manzannin Allah; wuta ce wadda za ta zame musu gidan dawwama da ba za ta yanke ba har abada, sakamako ne a gare su saboda sun yi ta musunta ayoyin Allah suka ƙi yin imani da su duk kuwa da bayyanar ƙarfin hujjar da ke cikinsu.
Allah kuma (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa bayan an jefa kafirai wuta a ranar alƙiyama manyansu da ƙanana, sai ƙananan su riƙa roƙon Allah da ya nuna musu waɗanda suka ɓatar da su daga cikin aljannu da mutane, watau kamar Iblis wanda shi ne jagoransu wanda ya sunnanta kafirci da saɓon Allah a bayan ƙasa shi da sauran shaiɗanu mabiyansa daga jinsin mutane da aljannu, domin su saka su a ƙarƙashin dugadugansu a wuta don su zamanto a can ƙasan ƙasa a wulaƙance cikin azaba mai tsanani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsayuwa kyam a kan shari'a babban abu ne mai matsayi a wurin Allah mai matsayi.

2. Karramawar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi wa bayinsa muminai da yadda yake jiɓintar sha'aninsu da na waɗanda za su rasu su bari.

3. Cikakkiyar ni'imar ɗan Aljanna, kuma duk abin da yake so zai samu.

Suratu Fussilat (30-32)
إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُواْ رَبُّنَا ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسۡتَقَٰمُواْ تَتَنَزَّلُ عَلَيۡهِمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ أَلَّا تَخَافُواْ وَلَا تَحۡزَنُواْ وَأَبۡشِرُواْ بِٱلۡجَنَّةِ ٱلَّتِي كُنتُمۡ تُوعَدُونَ ٣٠ نَحۡنُ أَوۡلِيَآؤُكُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِۖ وَلَكُمۡ فِيهَا مَا تَشۡتَهِيٓ أَنفُسُكُمۡ وَلَكُمۡ فِيهَا مَا تَدَّعُونَ ٣١ نُزُلٗا مِّنۡ غَفُورٖ رَّحِيمٖ ٣٢

30. Lalle waɗanda suka ce: "Allah ne Ubangijinmu", sannan suka tsaya kyam, to mala'iku za su sauko musu (lokacin mutuwa suna cewa): "Kada ku tsorata, kuma kada ku yi baƙin ciki, kuma ku yi farin ciki da Aljanna wadda kuka kasance ana yi muku alƙawarinta.

31. "Mu masoyanku ne a rayuwar duniya da kuma ta lahira; kuma a cikinta (Aljanna) za ku sami duk abin da rayukanku suke marmari, za kuma ku sami duk abin da kuke nema a cikinta.

32. "Liyafa ce daga (Allah) Mai gafara, Mai jin ƙai."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon bayinsa ne muminai waɗanda suka ce Allah ne kaɗai Ubangijinsu, ba su da wani abin bauta ba shi ba, suka kuma tsaya kyam a kan tafarkinsa miƙaƙƙe, suna aiki da umarninsa suna guje wa haninsa. To waɗannan idan lokacin mutuwarsu ya zo mala'iku ne za su sauko musu suna lallashin su suna kwantar musu da hankali da cewa, kada su ji tsoron mutuwa ko abin da zai biyo bayanta, kada kuma su yi baƙin cikin abin da za su bari a duniya, sai su yi musu albishir da gidan Aljanna wanda aka yi musu alƙawari da shi a duniya saboda imaninsu da kyawawan ayyukansu.
Mala'ikun za su ƙara tabbatar musu cewa, su masoyansu ne a duniya, su ne suka riƙa kwaɗaitar da su a kan aikata ayyukan alheri da bin gaskiya, su ne kuma suka riƙa ba su kariya; hakanan kuma a lahira su ne masoyansu suna tare da su ba za su bar su ba. Sai su kwaɗaitar da su ni'imar Aljanna da cewa za su sami duk abin da rayukansu za su yi sha'awa na kayan marmari a gidan Aljanna da abubuwan morewarta, duk kuma wani abu da za su yi sha'awa su nema za a kawo musu shi nan take. Wannan kuwa duka masaukin baƙi ne daga Allah mai gafarta zunuban bayinsa da suka tuba, kuma mai rahama gare su.

An karɓo daga Sufyan ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ce: "Ya Manzon Allah, ka faɗa mini wata magana a Musulunci wadda bayanka ba zan sake tambayar wani a kanta ba?" Sai ya ce: "Ka ce: Na yi imani da Allah, sannan sai ka tsaya kyam (a kanta)." [Muslim #62].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mala'iku suna halarto wa mamaci, idan ya kasance mutum ne nagari sai su ce: "Ka fito ya kai wannan rai mai tsarki da ke cikin jiki mai tsarki, ka fito kana abin yabo, ka yi farin cikin haɗuwa da hutu da ƙamshi da Ubangiji da ba mai fushi da kai ba. Haka za su yi ta faɗa har wannan ran ya fita, sannan a yi sama da shi…" [Ahmad #8768].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da matsayin masu da'awa zuwa ga Allah.

2. Abu ne mai matuƙar muhimmanci Musulmi ya riƙa alfahari da addininsa na Musulunci a ko'ina.

3. Haƙuri da juriya da rama mugunta da alheri halaye ne masu muhimmanci ga duk wani mai kira zuwa ga Allah.

4. Rama mugunta da alheri yana da matuƙar wahala ga ɗan'adam, domin an halicci zuciya da son rama mugunta da mugunta da rashin yin afuwa a kai, to ballanta kuma a zo da maganar rama mugunta da abu mafi alheri. To amma idan bawa ya haƙurƙurtar da zuciyarsa ya bi umarnin Ubangijinsa, zai gane cewa idan ya rama mugunta da mugunta babu abin da zai ƙaru da shi, kuma babu abin da zai wanzu tsakaninsa da maƙiyansa sai ƙiyayya. Amma idan ya kyautata masa wannan ba zai rage masa dukiyarsa ba, sai dai martabarsa ta ƙaru a wurin Allah, domin duk wanda ya ƙaskantar da kansa don Allah to Allah zai ɗaukaka shi.

5. Ba a iya samun kariya daga maƙiyi aljani ta hanyar kyautata masa, sai dai ta hanyar neman tsari daga Allah game da sharrinsa da waswasinsa.

Suratu Fussilat (33-36)
وَمَنْ أَحْسَنُ قَوْلًا مِّمَّن دَعَآ إِلَى ٱللَّهِ وَعَمِلَ صَٰلِحًا وَقَالَ إِنَّنِى مِنَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿٣٣﴾ وَلَا تَسْتَوِى ٱلْحَسَنَةُ وَلَا ٱلسَّيِّئَةُ ۚ ٱدْفَعْ بِٱلَّتِى هِىَ أَحْسَنُ فَإِذَا ٱلَّذِى بَيْنَكَ وَبَيْنَهُۥ عَدَٰوَةٌ كَأَنَّهُۥ وَلِىٌّ حَمِيمٌ ﴿٣٤﴾ وَمَا يُلَقَّىٰهَآ إِلَّا ٱلَّذِينَ صَبَرُوا۟ وَمَا يُلَقَّىٰهَآ إِلَّا ذُو حَظٍّ عَظِيمٍ ﴿٣٥﴾ وَإِمَّا يَنزَغَنَّكَ مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ نَزْغٌ فَٱسْتَعِذْ بِٱللَّهِ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٣٦﴾

33. Wane ne ya fi kyakkyawar magana fiye da wanda ya yi kira zuwa ga Allah ya kuma yi aiki nagari, kuma ya ce: "Lalle ni ina daga cikin Musulmi?"

34. Kyakkyawan (abu) da mummuna ba za su zama ɗaya ba. To ka ture mummuna da abin da ya fi kyau, to sai ka ga wanda yake tsakaninsa da kai gaba ce, ya zamanto kamar wani masoyi ne na ƙut da ƙut.

35. Ba kowa ake bai wa wannan kyakkyawar ɗabi'ar ba sai waɗanda suka yi haƙuri, ba kowa ake bai wa ita ba sai mai babban rabo.

36. Idan kuma wani tunzuri daga Shaiɗan ya tunzura ka, to sai ka nemi tsari daga Allah; lalle Shi Mai ji ne, Masani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafa gwiwar masu kira zuwa gare shi, da nuna girman matsayinsu a wurinsa da bayanin wasu kyawawan siffofi nasu, da cewa babu mutumin da ya fi kyakkyawar magana kamar wanda ya haɗa waɗannan siffofi uku:
Ta ɗaya, ya yi kira zuwa ga Allah, watau kaɗaita shi da yin biyayya gare shi.
Ta biyu, ya yi aiki nagari ya kuma nisanci munanan ayyuka.
Ta uku, ya yi alfahari da kasancewarsa Musulmi, yana mai aiki irin na Musulunci.
To duk wanda ya yi haka ya fi kowa kyakkyawar magana.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya kamata Musulmi ya kyautata alaƙarsa da sauran mutane, da cewa kyakkyawan aiki da Allah yake so ya kuma yarda da shi ba zai zama ɗaya da

mummunan aiki wanda Allah ba ya so ba. Sai Allah ya yi umarni ga duk mutumin da aka yi masa mummunan abu, to shi ya saka da sakamako mafi kyau; idan har ya aikata haka to zai ga wanda yake maƙiyinsa ne a can baya ya dawo ya zama masoyinsa, kamar ɗan'uwa na kusa ƙut da ƙut.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman falalar wannan kyakkyawar ɗabi'a da cewa, babu wanda yake dacewa da ita sai masu haƙurin gaske a kan cutarwa da musgunawar da ake yi musu, sai kuma mutum mai babban rabo, saboda ɗimbin alheri da ke cikin wannan kyakkyawan hali.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci hanyar magance sharrin Shaiɗan idan ya yi ƙoƙarin kautar da mutum daga wannan koyarwa mai matuƙar amfani, ya fara yi masa waswasi da miyagun saƙe-saƙe, to sai ya nemi tsarin Allah da kariyarsa daga sharrin Shaiɗan, domin Allah yana jin duk abin da yake faɗi, yana kuma sane da halin da yake ciki, saboda shi mai ji ne masani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da Tauhidi ta hanyar ƙarfafan dalilai waɗanda babu kokwanto a cikinsu, masu tabbatar da cewa Allah ne kaɗai ya cancanta a bauta masa ba wani cikin halittunsa ba.

2. Tabbatar da yiwuwar tashi bayan mutuwa, kamar yadda ake raya ƙasa bayan mutuwarta.

3. Duk girman abin halitta da yawan amfaninsa ba zai cancanci a bauta masa ba. Bauta tana kasancewa ne ga Allah mahalicci shi kaɗai.

4. Bayanin yawan ibadar mala'iku da cikakkiyar biyayyarsu ga Allah, da tabbatar da cewa Allah ba ya da buƙatar wani daga cikin halittarsa.

Suratu Fussilat (37-39)
وَمِنْ ءَايَٰتِهِ ٱلَّيْلُ وَٱلنَّهَارُ وَٱلشَّمْسُ وَٱلْقَمَرُ ۚ لَا تَسْجُدُوا۟ لِلشَّمْسِ وَلَا لِلْقَمَرِ وَٱسْجُدُوا۟ لِلَّهِ ٱلَّذِى خَلَقَهُنَّ إِن كُنتُمْ إِيَّاهُ تَعْبُدُونَ ﴿٣٧﴾ فَإِنِ ٱسْتَكْبَرُوا۟ فَٱلَّذِينَ عِندَ رَبِّكَ يُسَبِّحُونَ لَهُۥ بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَهُمْ لَا يَسْـَٔمُونَ ﴿٣٨﴾ وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنَّكَ تَرَى ٱلْأَرْضَ خَٰشِعَةً فَإِذَآ أَنزَلْنَا عَلَيْهَا ٱلْمَآءَ ٱهْتَزَّتْ وَرَبَتْ ۚ إِنَّ ٱلَّذِىٓ أَحْيَاهَا لَمُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰٓ ۚ إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٣٩﴾

37. Kuma dare da wuni da rana da wata suna daga ayoyinsa. Kada ku yi sujjada ga rana ko ga wata, ku yi sujjada ga Allah Wanda Ya halicce su idan har kun kasance Shi kaɗai kuke bauta wa.

38. Idan kuwa sun yi girman kai, to waɗanda suke wurin Ubangijinka (mala'iku) suna yi masa tasbihi dare da rana, kuma su ba sa ƙosawa.

39. Yana kuma daga ayoyinsa cewa lalle za ka ga ƙasa a ƙeƙashe, to idan Mun saukar mata da ruwa sai ta girgiza ta kumbura (ta fitar da tsirrai). Lalle wanda Ya raya ta Shi ne Mai raya matattu. Lalle Shi Mai iko ne a kan komai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin ƙarfafan hujjoji a kan cikar Kudurarsa da Kaɗaitakarsa, da cewa daga cikin manyan ayoyinsa masu nuna girmansa da Kaɗaitakarsa akwai jujjuyawar dare da yini, wannan ya zo wannan ya tafi, da rana da wata waɗanda rayuwar ɗan'adam a bayan ƙasa ba za ta yiwu ba sai da su. Duk waɗannan ayoyi ne masu nuna Allah ne kaɗai abin bauta, don haka ya kira mutane da cewa kada su yi wa rana da wata sujjada, sai dai su yi sujjada ga Allah shi kaɗai wanda ya halicce su in dai shi kaɗai suke bauta wa da gaske.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa idan mushirikai suka yi girman kai suka bijire wa bautar Allah shi kaɗai, suka ƙi yarda su yi masa sujjada a matsayinsa na mahaliccin komai, to su sani babu abin da za su cutar da Allah da shi, domin mala'iku da suke wurinsa suna yi masa tasbihi tare da gode masa ba dare ba rana, kuma ba sa ƙosawa daidai da ƙiftawar ido.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasu hujjoji na cikar Kudurarsa da ke bayan ƙasa, da cewa daga cikin manyan ayoyinsa masu nuna cikar Kaɗaitakarsa da kuma yiwuwar tashin alƙiyama, mutum zai ga ƙasa a ƙeƙashe babu tsiro a kanta, to amma da zarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar mata da ruwan sama, sai a ga ta kumbura ta motsa ƙwayoyin da ke cikinta sun tsiro har sun ɗago sama. Lalle wanda ya iya raya wannan matacciyar ƙasa har ta fito da tsironta, to zai iya raya matattu don yi musu hisabi ranar alƙiyama, domin shi Allah mai iko ne a kan komai babu abin da yake gagarar sa a ƙasa ko a sama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin fanɗare wa ayoyin Allah ta hanyar ƙaryata su ko canza musu ma'ana.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa ɗan'adam dama ta ya zabi abin da yake so, bayan ya ji bayanin gaskiya da ƙarya da sakamakon kowannensu. Don haka ba a yi masa tilas ba a kan ayyukan da yake yi, duk kuwa da kasancewarsa ba zai iya fita daga *mashi'ar* Allah ba.

3. Tabbatar da cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Alƙur'ani kyakkyawan tsaro, babu mai iya gurɓata shi har zuwa ranar komawa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Fussilat (40-43)
إِنَّ ٱلَّذِينَ يُلۡحِدُونَ فِيٓ ءَايَٰتِنَا لَا يَخۡفَوۡنَ عَلَيۡنَآۗ أَفَمَن يُلۡقَىٰ فِي ٱلنَّارِ خَيۡرٌ أَم مَّن يَأۡتِيٓ ءَامِنٗا يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ ٱعۡمَلُواْ مَا شِئۡتُمۡ إِنَّهُۥ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٌ ٤٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِٱلذِّكۡرِ لَمَّا جَآءَهُمۡۖ وَإِنَّهُۥ لَكِتَٰبٌ عَزِيزٞ ٤١ لَّا يَأۡتِيهِ ٱلۡبَٰطِلُ مِنۢ بَيۡنِ يَدَيۡهِ وَلَا مِنۡ خَلۡفِهِۦۖ تَنزِيلٞ مِّنۡ حَكِيمٍ حَمِيدٖ ٤٢ مَّا يُقَالُ لَكَ إِلَّا مَا قَدۡ قِيلَ لِلرُّسُلِ مِن قَبۡلِكَۚ إِنَّ رَبَّكَ لَذُو مَغۡفِرَةٖ وَذُو عِقَابٍ أَلِيمٖ ٤٣

40. Lalle waɗanda suke fanɗara game da ayoyinmu, ba za su ɓoyu gare Mu ba. Yanzu wanda za a jefa shi a cikin wuta, shi ya fi ko kuma wanda zai zo yana amintacce a ranar alƙiyama? Ku aikata abin da kuka ga dama, lalle Shi Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

41. Lalle waɗanda suka kafirce wa Alƙur'ani lokacin da ya zo musu (tabbas Allah zai saka musu). Lalle kuma shi littafi ne mabuwayi.

42. Ɓarna ba ta zuwa masa ta gabansa ko kuma ta bayansa; saukakke ne daga Mai hikima, Sha-yabo.

43. Ba abin da ake faɗa maka sai irin abin da aka faɗa wa manzanni a gabaninka. Lalle Ubangijinka Mai gafara ne, kuma Mai uƙuba mai raɗaɗi ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi kafirai waɗanda suke fanɗare wa ayoyinsa, suna ƙaryata su, suna musunta su da jirkita ma'anoninsu ko canja lafuzansu, da cewa ba za su iya ɓoye masa ba, yana sane da duk abin da suke aikatawa kuma za su ga sakamakonsu, watau wutar Jahannama. Kuma su sani cewa ba za a gwada wanda za a jefa shi cikin wuta ranar alƙiyama da wanda zai zo yana amintacce ba. Sai kuma ya sake tsoratar da su da cewa su je su aikata duk abin da suka ga dama mai kyau ko mummuna, ya rage nasu, shi kuwa Allah mai ganin duk abin da suke aikatawa ne, kuma zai musu sakayya a kai.

Waɗannan fanɗararru kuma masu kafirce wa Alƙur'ani lokacin da ya zo musu daga Allah, lalle azaba mai tsanani ta tabbata a kansu ranar alƙiyama.
Sai kuma Allah ya ambaci wasu siffofi na Alƙur'ani guda uku:
Siffa ta ɗaya, shi littafi ne mabuwayi, babu wanda zai iya jirkita shi ko canja shi.
Ta biyu, ɓarna ba ta zuwa masa ta gabansa ko ma ta bayansa, watau babu wanda ya isa ya ƙara wani abu a cikinsa ko ya rage, dukkansa gaskiya ce tsantsa.
Ta uku, saukakke ne daga Allah mai hikima Sha-yabo, watau duk abin da ya ƙunsa cike yake da hikima da maslaha ga halittun Allah, don haka babu makusa tare da shi, duk wani mai hankali zai yi sambarka da abin da ya zo cikinsa na shari'a da koyarwa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin Annabi Muhammadu (ﷺ) don ya ci gaba da abin da yake kai na kira zuwa ga Allah, har ya gama isar da saƙon da aka aiko shi da shi.

2. Yanke wa mushirikai hanzari, don haka ya saukar da Alƙur'ani da harshen da suke fahimta.

3. Kore wa Allah zalunci da tabbatar masa sifar adalci.

Suratu Fussilat (44-46)
وَلَوۡ جَعَلۡنَٰهُ قُرۡءَانًا أَعۡجَمِيّٗا لَّقَالُواْ لَوۡلَا فُصِّلَتۡ ءَايَٰتُهُۥٓۖ ءَأَعۡجَمِيّٞ وَعَرَبِيّٞۗ قُلۡ هُوَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ هُدٗى وَشِفَآءٞۖ وَٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ فِيٓ ءَاذَانِهِمۡ وَقۡرٞ وَهُوَ عَلَيۡهِمۡ عَمًىۚ أُوْلَٰٓئِكَ يُنَادَوۡنَ مِن مَّكَانِۭ بَعِيدٖ ٤٤ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ فَٱخۡتُلِفَ فِيهِۚ وَلَوۡلَا كَلِمَةٞ سَبَقَتۡ مِن رَّبِّكَ لَقُضِيَ بَيۡنَهُمۡۚ وَإِنَّهُمۡ لَفِي شَكّٖ مِّنۡهُ مُرِيبٖ ٤٥ مَّنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَنۡ أَسَآءَ فَعَلَيۡهَاۗ وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ٤٦

44. Da Mun sanya shi Alƙur'ani Ba'ajame da tabbas za su ce: "Me ya hana a bayyana ayoyinsa? Yanzu (a ce Alƙur'ani) Ba'ajame (Annabi kuma) Balarabe?" Ka ce: "Shi ga waɗanda suka yi imani shiriya ne da waraka. Waɗanda kuwa ba sa yin imani akwai nauyi cikin kunnuwansu, shi kuma makanta ne a gare su." Waɗannan (sun yi kama da waɗanda) ake kira daga wuri mai nisa.

45. Haƙiƙa Mun bai wa Musa Littafin (Attaura), sai aka yi saɓani a cikinsa, kuma ba don Kalma ta gabata daga Ubangijinka ba, tabbas da an yi hukunci a tsakaninsu. Lalle kuma su, tabbas suna cikin shakka mai sa kokwanto a game da shi.

46. Wanda ya yi aiki nagari, to kansa ya yi wa, wanda kuma ya munana, to a kan kansa ya yi wa. Ubangijnka ba Mai zaluntar bayi ba ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzo (ﷺ) game da ƙaryatawar da mutanensa suke yi masa da cewa, ba shi ne farau ba, domin duk abin da za a faɗa masa na ƙaryatawa ko izgili to an faɗi irinsa ga manzannin da suka gabace shi, don haka ya ci gaba da haƙuri, domin Ubangijinsa mai gafara ne ga bayinsa da suka tuba suka bar laifin da suke aikatawa, kuma mai tsananin uƙuba ne ga duk wanda ya doge a kan aikata laifi ya ƙi tuba ga Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da amsa game da wani ruɗani da kafirai suke kawowa game da Alƙur'ani da cewa, wai me ya sa ba a saukar da shi da harshen Ajamanci ba, watau ba da Larabaci ba? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa da ya saukar da Alƙur'ani da wani harshe ba na Larabci ba, to da lalle kafirai za su ce: Me ya hana a bayyana ayoyinsa yadda za su fahimta? Za kuma su yi ta kwakwazon cewa yaya za a ce Manzo Balarabe littafin da aka saukar masa kuma Ba'ajame, watau wani harshe wanda

ba Larabci ba? Don haka sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya toshe musu baki, ba abin da za su iya faɗa na suka ga Alƙur'ani ba tare da an gane ƙaryarsu ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, shi Alƙur'ani ai shiriya ne daga ɓata ga waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa, kuma waraka ne ga jahilcin da ke cikin zukata. Amma su waɗanda ba su yi imani da Allah ba akwai kurumta a kunnuwansu, don haka ba sa iya jin gaskiya su bi ta, kuma shi Alƙur'ani makanta ne a gare su ba za su fahimce shi ba, ba kuma za su ga shiriyarsa ba. Allah ya tabbatar da cewa su waɗannan mutane sun yi kama da waɗanda ake kiran su daga wani wuri mai nisa da ba za su iya jin sautin mai kiran su ba ballantana su amsa masa, watau sun zama waɗanda suka yi nisa ne ba sa jin kira, kamar yadda Bahaushe yake cewa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa su waɗannan masu ƙaryata Alƙur'ani ai ba su ne farau ba wajen bijire wa saƙon Allah; gabaninsu Allah ya ɓai wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) littafin Attaura, to amma sai mutanensa suka yi ta saɓani game da shi, wasu suka yi imani suka gaskata cewa daga Allah yake, wasu kuma suka kafirce masa suka ƙaryata shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ba don ya riga ya yi alƙawarin cewa a ranar lahira zai yi hukunci tsakanin bayinsa ba, da tuni ya bayyana mai gaskiya da maƙaryaci a tsakaninsu tun a nan duniya, ya karrama mai gaskiya ya kuma wulaƙantar da maƙaryaci ya gaggauto masa uƙuba. To amma kafirai a kowane lokaci suna cikin shakka mai jefa su cikin tantama da rashin sanin alƙibla.
Sannan sai Allah ya bayyana sakamakon kowa gwargwadon aikinsa; wanda ya yi aiki nagari to kansa ya yi wa domin shi ne zai amfana da aikinsa, wanda kuma ya yi mummunan aiki to kansa ya cutar, domin shi Allah ba zai amfana da aikin wani ko ya cutu don aikin wani ba; zai saka wa kowa daidai da aikinsa, kuma ba zai zalunci bayinsa ba, ya rage wa wani ladan aikinsa nagari ko ya ƙara wa wani laifin da bai aikata ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ne kaɗai ya san lokacin zuwan ranar alƙiyama domin shi kaɗai ne masanin gaibu.

2. Ilimin Allah ya game komai da komai.

3. Ranar alƙiyama mushirikai masu bautar wanin Allah za su tabbatar da cewa aikin banza suka yi, kuma babu mai ceton su daga azabar Allah ko ya tserar da su.

Suratu Fussilat (47-48)
*إِلَيۡهِ يُرَدُّ عِلۡمُ ٱلسَّاعَةِۚ وَمَا تَخۡرُجُ مِن ثَمَرَٰتٖ مِّنۡ أَكۡمَامِهَا وَمَا تَحۡمِلُ مِنۡ أُنثَىٰ وَلَا تَضَعُ إِلَّا بِعِلۡمِهِۦۚ وَيَوۡمَ يُنَادِيهِمۡ أَيۡنَ شُرَكَآءِي قَالُوٓاْ ءَاذَنَّٰكَ مَامِنَّا مِن شَهِيدٖ ٤٧ وَضَلَّ عَنۡهُم مَّا كَانُواْ يَدۡعُونَ مِن قَبۡلُۖ وَظَنُّواْ مَا لَهُم مِّن مَّحِيصٖ ٤٨

47. Gare shi ne ake mayar da sanin lokacin alƙiyama. Kuma babu wasu 'ya'yan itatuwa da suke fitowa daga kwansonsu, babu kuma wata mace da take ɗaukan ciki ko take haifewa sai da saninsa. Kuma a ranar da zai yi kiran su cewa: "Ina abokan tarayyar tawa?" Za su ce: "Mun sanar da Kai (a yau) babu wani mai yin shaida daga cikinmu."

48. Kuma abin da suka kasance suna bauta wa a da ya ɓace musu, suka kuma tabbatar ba su da wata matsera.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ranar da zai yi wa kowa sakayya a cikinta rana ce da babu wanda ya san lokacin zuwanta sai shi kaɗai, domin shi ne yake da faffaɗan ilimin sanin komai da komai na abin da ya wuce da abin da zai zo nan gaba, faffaɗan iliminsa ne ma ya sanya babu wasu

‘ya’yan itatuwa da za su fito daga kwansonsu, babu kuma wata mace da za ta ɗauki ciki ko ta haihu sai da saninsa. To amma abin mamaki, me ya sa mushirikai suke haɗa shi da wasu abokan tarayya waɗanda ba su san komai ba? Lalle za su gane kurensu ranar da zai yi kiran su ya tambaye su ina abokan tarayyar nasa da suke daidaita shi da su. A ɓokacin ne za su yi iƙirari da cewa a cikinsu babu wani da zai ba da shaidar cewa Allah yana da abokin tarayya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a ranar duk wani abu da kafirai suke bautarsa ya ɓace musu ɓat; ba su ma gan shi ba ballantana har ya cece su kamar yadda suke zato. Daga nan za su tabbatar da cewa ba su da wata matsera daga azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin son ɗan’adam ga alheri da yawan rakinsa idan mummunan abu ya same shi, da fitar da ƙaunarsa daga rahamar Allah.

2. Butulcin kafiri game da ni’imar Allah da rashin godiyarsa gare shi wanda yake kai shi ga musunta ranar alƙiyama.

Suratu Fussilat (49-51)
لَّا يَسۡـَٔمُ ٱلۡإِنسَٰنُ مِن دُعَآءِ ٱلۡخَيۡرِ وَإِن مَّسَّهُ ٱلشَّرُّ فَيَـُٔوسٞ قَنُوطٞ ٤٩ وَلَئِنۡ أَذَقۡنَٰهُ رَحۡمَةٗ مِّنَّا مِنۢ بَعۡدِ ضَرَّآءَ مَسَّتۡهُ لَيَقُولَنَّ هَٰذَا لِي وَمَآ أَظُنُّ ٱلسَّاعَةَ قَآئِمَةٗ وَلَئِن رُّجِعۡتُ إِلَىٰ رَبِّيٓ إِنَّ لِي عِندَهُۥ لَلۡحُسۡنَىٰۚ فَلَنُنَبِّئَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِمَا عَمِلُواْ وَلَنُذِيقَنَّهُم مِّنۡ عَذَابٍ غَلِيظٖ ٥٠ وَإِذَآ أَنۡعَمۡنَا عَلَى ٱلۡإِنسَٰنِ أَعۡرَضَ وَنَـَٔا بِجَانِبِهِۦ وَإِذَا مَسَّهُ ٱلشَّرُّ فَذُو دُعَآءٍ عَرِيضٖ ٥١

49. Mutum ba ya ƙosawa wajen roƙon alheri, idan kuwa wani sharri ya same shi, to sai ya zama mai tsananin ɗebe ƙauna.

50. Tabbas kuma idan Muka ɗanɗana masa wata rahama tamu bayan wata cuta da ta same shi, tabbas zai riƙa cewa: “Wannan nawa ne, kuma ba na tsammanin alƙiyama za ta tashi, kuma tabbas idan ma da za a mayar da ni zuwa ga Ubangijina, lalle zan zama mai samun mafi kyan sakamako a wurinsa.” To tabbas za Mu saka wa waɗanda suka kafirta da abin da suka aikata, kuma tabbas za Mu ɗanɗana musu azaba mai gwabi.

51. Idan kuma Muka yi wa mutum ni’ima sai ya bijire ya ja jikinsa nesa (daga tuna Allah), kuma idan sharri ya same shi, sai ya zama mai faffaɗar addu’a.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani mummunan hali na ɗan’adam na raki da butulci, da cewa shi ɗan’adam ba ya ƙosawa wajen roƙon alheri, kamar lafiya da dukiya da ‘ya’ya da sauran ni’imomi, to amma da zarar mummunan abu ya same shi, kamar talauci ko rashin lafiya, to sai ya zama mai yawan ɗebe ƙauna daga rahamar Allah, ya zaci wannan abu da ya same shi zai zama shi ne hallakarsa.
Haka kuma idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗanɗana masa wata rahama daga gare shi, kamar lafiya ko wadata, bayan wata cutar da ta same shi da farko, to zai riƙa cika baki yana cewa, wannan abu da aka ba shi da man can nasa ne, ya kuma cancanci a ba shi, sai ya butulce wa Allah ya shiga musunta tashin ƙiyama yana da’awar cewa ba za ta zo ba, kuma wai idan da gaske ne za ta zo, to sai ya tabbatar da cewa, a can ma sai ya sami ni’imar da ta fi ta duniya, domin a ganinsa ya cancanci haka, shi ya sa aka ba shi irinta a nan duniya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar masa da martani cewa tabbas zai ba wa kafirai labarin duk abin da suka aikata a nan duniya na kafirci da saɓonsa, kuma tabbas sai ya ɗanɗana musu azaba mai tsanani.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana butulcin ɗan'adam bayan ni'ima da Allah ya yi masa, watau sai ya bijire wa ambaton Allah da godiya a gare shi, ya ja jikinsa nesa ya daina tuna Allah wanda shi ne ya ba shi wannan ni'imar, don nuna girman kai da taƙadaranci. To amma kuma da zarar ya shiga wani mummunan hali na rashin lafiya ko talauci, to sai ya duƙufa ga addu'a yana roƙon Allah ya yaye masa bayan a da ya ƙi gode wa Allah ni'imomin da ya yi masa sannan kuma yanzu ya kasa haƙuri a kan jarrabar da Allah ya yi masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu ɓatacce kamar mai ƙaryata Alƙur'ani, saboda yana rayuwa ne cikin ruɗani da saɓani.

2. Babu wani abu da ɗan'adam zai gano na ayoyin Allah a sasannin duniya da halittar ɗan'adam face yana ƙarƙashin aya ta 53 ta wannan Sura.

3. Ba da daɗewa ba za a gane ingancin addinin Musulunci, kuma a kwana a tashi mutane za su yi ta karɓar sa.

4. Tabbatar da tashi bayan mutuwa da sakamako a kan ayyuka.

5. Ilimin Allah da Kudurarsa sun kewaye komai.

Suratu Fussilat (52-54)
قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِن كَانَ مِنۡ عِندِ ٱللَّهِ ثُمَّ كَفَرۡتُم بِهِۦ مَنۡ أَضَلُّ مِمَّنۡ هُوَ فِي شِقَاقِۭ بَعِيدٖ ۝٥٢ سَنُرِيهِمۡ ءَايَٰتِنَا فِي ٱلۡأٓفَاقِ وَفِيٓ أَنفُسِهِمۡ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَهُمۡ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّۗ أَوَ لَمۡ يَكۡفِ بِرَبِّكَ أَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ۝٥٣ أَلَآ إِنَّهُمۡ فِي مِرۡيَةٖ مِّن لِّقَآءِ رَبِّهِمۡۗ أَلَآ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَيۡءٖ مُّحِيطُۢ ۝٥٤

52. Ka ce: "Ku ba ni labari, idan (Alƙur'ani) ya kasance daga wajen Allah, sannan kuka kafirce masa, to wane ne ya fi ɓata fiye da wanda yake cikin saɓani mai nisa?"

53. Ba da daɗewa ba za Mu nuna musu ayoyinmu a cikin nahiyoyi da kuma a kan kawunansu har sai sun gane cewa lalle shi (Alƙur'ani) gaskiya ne. Yanzu bai ishe ka ba game da Ubangijinka cewa Shi lalle Mai shaida ne a kan komai?

54. Ku saurara, lalle su suna cikin kokwanto ne game da haɗuwa da Ubangijnsu. Ku saurara, lalle Shi Mai kewaye komai ne da saninsa.

A ayoyi na ƙarshen wannan Sura Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya tambayi kafirai masu ƙaryata Alƙur'ani cewa, idan Alƙur'ani ya zama tabbas daga Allah yake sannan su kuma suka kafirce masa, suka ƙaryata shi, to yaya suke tsammanin lamarinsu zai kasance? Sai Allah ya bayyana cewa babu wanda ya fi ɓata fiye da wanda yake jayayya da taurin kai game da gaskiya duk da cewa hujja ta bayyana a gare shi a fili.
Sai kuma Allah ya tabbatar wa kafirai cewa zai nuna musu ayoyinsa a cikin nahiyoyin ƙasa daga garuruwan da zai ba wa Musulmi nasara su kama su. A kan kawunansu ma zai nuna musu ayoyinsa yayin da zai ba wa Musulmi nasarar cinye Makka da yaƙi, har su gane cewa Alƙur'ani gaskiya ne babu wani kokwanto a cikinsa. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tambayar cewa, shin yanzu bai ishi mushirikai ba su gane cewa Alƙur'ani gaskiya ne saboda ganin cewa Allah ne (Mai tsarki da ɗaukaka) da kansa ya ba da shaida a kan

cewa shi gaskiya ne? To akwai shaidar da ta kai ta Allah ne? Ai tabbas da a ce su masu son gaskiya ne da shaidar Allah ta ishe su.
Sai kuma Allah ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa, lalle mushirikai suna cikin kokwanto ne na gamuwa da Ubangijinsu ranar alƙiyama saboda ba su yarda da zuwanta ba, shi ya sa ma ba sa yi mata wani kyakkyawan tanadi, lalle kuma Allah ya kewaye komai da saninsa da ikonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman matsayin Alƙur'ani da zamantowarsa mu'ujiza gagara-koyo.

2. Annabi (ﷺ) ba wani ne daban da sauran annabawan da Allah ya aiko ba, shi ma Allah yana yi masa wahayi ne kamar yadda ya yi wa waɗancan annabawan, don haka aiko shi bai zama abin mamaki ba.

3. Bayanin girman Allah da cikar Kudurarsa da ikonsa.

4. Addu'ar mala'iku ta neman gafarar Allah ga muminai a bayan ƙasa.

5. Lallashin Manzon Allah (ﷺ) game da rashin imanin mutanensa da taurin kansu da nuna masa cewa, kada ya damu kansa game da su, domin Allah yana sane da duk abin da suke aikatawa, shi kuma Annabi babu mai yi masa tambaya a kan abin da suke aikatawa.

42-Suratus Shura

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran wannan Sura da ‘Suratus Shura’, kamar yadda yake a cikin *masahifu* da littafan tafsirai masu yawa, saboda lafazin ' ***Shura*** ' da ya zo a cikinta a aya ta 37.
Hakanan akan kira ta da *‘Suratu Ha Mim Ain Sin Kaf’* kamar yadda ya zo a cikin *Sahihu*l Bukhari da **Jami’ut Tirmizi** da littattafan tafsiri.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* gaba ɗayanta a wurin yawancin malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta sittin da tara (69) a jerin saukar surorin Alƙur’ani. Ta sauka bayan *‘Suratul Kahfi*’ gabanin ‘*Suratu Ibrahim*’.

4. Adadin ayoyinta:
A lissafin mutanen Kufa adadin ayoyinta hamsin da uku ne (53). A wurin mutanen Madina da Makka da Sham da Basra kuwa hamsin ne (50).

5. Babban Jigonta:
Tana bayani a kan haƙiƙanin wahayi da kuma tabbatar da manzancin Annabi (ﷺ) da nuna cewa shi ma ɗaya ne daga cikin manzannin da Allah ya aiko.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Bayanin matsayin Alƙur’ani da kasancewarsa mu’ujiza da ta gagari kowa.
• Tabbatar wa mushirikai cewa wahayin da aka yi wa Manzo (ﷺ) shi ne irin wahayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa manzanninsa gabaninsa.
• Bayanin cewa mushirikai masu ƙaryata Manzo (ﷺ) ba su da wata hujja ta yin haka sai koyi da shugabanninsu na kafirci waɗanda suke jaye da ragamarsu.
• Tsoratar da mushirikai ranar alƙiyama da abubuwan da ta ƙunsa na mummunan sakamako ga waɗanda suka bijire wa Allah da manzanninsa, da kuma kyakkyawan sakamako ga waɗanda suka bi Allah da manzanninsa.
• Ambaton ƙarfafan dalilai masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah da kuma ni’imomi daban-daban da ya yi wa mutane waɗanda wajibi ne su gode masa a kansu.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da nuna masa cewa Allah ne zai yi sakayya ga masu ƙaryata shi. Don haka kada ya daka ta tasu, ya dai ci gaba da kira zuwa ga Allah tare da nuna musu wajabcin kula da zumuncin da ke tsakaninsa da su.
• Tunatar da su ni’imomin da Allah ya yi musu da jan hankalinsu a kan kiyaye wannan ni’imar don kada miyagun ayyukansu su ja su har su rasa ta gaba ɗaya.

• Tunatar da su girman shiriyar da Annabi (ﷺ) ya zo musu da ita, duk da suna sane da cewa tun farkon tasowarsa a cikinsu bai taɓa da'awar wani wahayi ba ko cewa yana kan wata shiriya sai bayan da Allah ya yi masa wahayin Alƙur'ani. Wannan kaɗai ya isa ya nuna gaskiyarsa.

Suratus Shura (1-6)

حمٓ ﴿١﴾ عٓسٓقٓ ﴿٢﴾ كَذَٰلِكَ يُوحِيٓ إِلَيۡكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكَ ٱللَّهُ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ﴿٣﴾ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡعَظِيمُ ﴿٤﴾ تَكَادُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرۡنَ مِن فَوۡقِهِنَّۚ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ يُسَبِّحُونَ بِحَمۡدِ رَبِّهِمۡ وَيَسۡتَغۡفِرُونَ لِمَن فِي ٱلۡأَرۡضِۗ أَلَآ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٥﴾ وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ ٱللَّهُ حَفِيظٌ عَلَيۡهِمۡ وَمَآ أَنتَ عَلَيۡهِم بِوَكِيلٖ ﴿٦﴾

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ha Mim.

2. Ain Sin Kaf.

3. Kamar haka ne Allah Mabuwayi, Mai hikima Yake yi maka wahayi da kuma waɗanda suka gabace ka.

4. Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne; kuma Shi Maɗaukaki ne, Mai girma.

5. Sammai suna neman su tsattsage ta samansu (don girmansa). Mala'iku kuma suna yin tasbihi da yabon Ubangijinsu, suna kuma neman gafara ga waɗanda suke cikin ƙasa. Ku saurara, Lalle Allah Shi ne Mai gafara, Mai rahama.

6. Waɗanda kuwa suka riƙi wasu majiɓinta ba shi ba, Allah Mai kiyaye da su ne, kai kuma ba wakili ne ba a kansu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori gabaninta da irin waɗannan haruffan. [Dubi tafsirinmu na farkon *Suratul Baƙara* domin ƙarin bayani].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, wahayin da ya yi masa irinsa ne ya yi wa annabawan da suka gabace shi. Allah ne mabuwayi wanda ya fi ƙarfin kowa, babu mai iya ja da shi, kuma mai hikima cikin dukkan al'amuransa na halitta da na shari'a.
Allah kuma ya bayyana cewa, duk abin da yake cikin sammai da ƙasa nasa ne, halittarsa ce, mulkinsa ne kuma bayinsa ne. Shi ne kuma Maɗaukaki da Zatinsa da siffofinsa da Kudurarsa da rinjayensa, mai girma ne, wanda saboda girmansa sammai suna neman su tsattsage daga saman ƙassai, suna kuma cike da mala'iku waɗanda suke tasbihi suna tsarkake Ubangijinsu tare da yabon sa da gode masa, don nuna girmamawarsu a gare shi. Suna kuma neman gafara daga Allah ga muminai da suke bayan ƙasa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa shi mai gafara ne ga bayinsa da suka tuba daga zunubansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi masu bautar wasu ba shi ba, da cewa yana sane da duk abin da suke ciki, kuma yana ƙididdige ayyukansu, kuma shi zai yi musu sakayya a kansu, bai ɗora wa Manzonsa nauyin kula da ayyukansu ba, don haka ba wanda zai yi masa tambaya a kan ayyukansu sai dai a tambaye shi game da isar musu da saƙon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani Balaraben littafi ne, don haka koyon harshen Larabci muhimmi ne ga Musulmi domin fahimtar saƙon Allah.

2. Saƙon Manzon Allah (ﷺ) bai taƙaita ga Larabawan Makka kaɗai ba; ya shafi dukkan mutanen duniya baki ɗaya. An keɓance mutanen Makka da waɗanda suke kewaye da su ne aka yi musu gargaɗi, domin su ne maƙasudin wannan martani a nan, saboda sun musunta manzancin Annabi (ﷺ) sun yi jayayya da shi.

3. Tsoratarwa game da ranar alƙiyama da tabbatar da zuwanta.

4. Karkasuwar mutane a ranar alƙiyama zuwa ƙungiyoyi biyu, ƙungiyar ‘yan Aljanna da ƙungiyar ‘yan wuta.

5. Hikimar Allah ta kasa mutane kashi biyu, ‘yan Aljanna da ‘yan wuta, domin girman rahamar Allah ta bayyana ga muminai da ya ba su shiriya, su kuma azzalumai su gane munin sakamakon zalunci.

Suratus Shura (7-8)
وَكَذَٰلِكَ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ قُرۡءَانًا عَرَبِيّٗا لِّتُنذِرَ أُمَّ ٱلۡقُرَىٰ وَمَنۡ حَوۡلَهَا وَتُنذِرَ يَوۡمَ ٱلۡجَمۡعِ لَا رَيۡبَ فِيهِۚ فَرِيقٞ فِي ٱلۡجَنَّةِ وَفَرِيقٞ فِي ٱلسَّعِيرِ ٧ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَهُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَلَٰكِن يُدۡخِلُ مَن يَشَآءُ فِي رَحۡمَتِهِۦۚ وَٱلظَّٰلِمُونَ مَا لَهُم مِّن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٍ ٨

7. Kuma kamar haka Muka yiwo maka wahayin Alƙur’ani Balarabe, don ka gargaɗi mutanen Makka da waɗanda suke kewaye da ita (watau duniya baki ɗaya), ka kuma yi gargaɗin ranar taruwa da babu kokwanto a game da ita. Wata ƙungiya tana cikin Aljanna, wata ƙungiya kuma tana cikin wutar Sa’ira.

8. Da kuma Allah Ya ga dama da Ya sanya su al’umma ɗaya (watau a kan addini ɗaya), sai dai kuma Yana shigar da wanda Ya ga dama cikin rahamarsa. Azzalumai kuma ba su da wani majiɓinci ko wani mataimaki.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya yi wa Manzon Allah (ﷺ) wahayi kamar sauran annabawan da suka gabace shi, ya saukar masa da Alƙur’ani cikin harshen Larabci don al’ummarsa su fahimce shi, ya kuma yi musu gargaɗi da shi, su da sauran garuruwan Larabawa da suke kewaye da Makka da sauran mutanen duniya baki ɗaya. Ya gargaɗe su game da ranar alƙiyama, ranar da Allah zai tattara halittun farko da na ƙarshe a farfajiya guda ɗaya domin yi musu hisabi da sakamako. Wannan ranar babu makawa sai ta zo, kuma mutane za su kasu gida biyu a cikinta, wasu su tafi Aljanna su ne muminai; wasu kuma su tafi wuta su ne kafirai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya fito gare mu yana ɗauke da wasu littattafai biyu a hannunsa sai ya ce: “Shin ko kun san waɗanne littattafai ne waɗannan?” Sai muka ce: “A’a, sai in ka faɗa mana ya Manzon Allah.” Sai ya ce dangane da wanda yake a hannunsa na dama: “Wannan littafi ne daga Ubangijin halittu yana ɗauke da sunayen ‘yan Aljanna da sunayen iyayensu da ƙabilunsu, an tattara su duka har na ƙarshensu, ba za a ƙara su ba, ba kuma za a rage su ba har abada.” Sannan dangane da na hannun hagunsa sai ya ce: “Wannan littafin ‘yan wuta ne da sunayensu da sunayen iyayensu da ƙabilunsu, an tattara su duka har zuwa na ƙarshensu, ba za a ƙara su ba, ba kuma za a rage su ba har abada.” Sai sahabbai suka ce: “To tunda abin haka yake don mene ne muke yin aiki idan har an riga an gama yanke komai?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce musu: “Ku daidaita ayyukanku kuma ku kwatanta bakin gwargwado, domin ɗan Aljanna zai cika ne da aikin 'yan Aljanna, ko ma wane aiki ya aikata (a baya), shi ma kuma ɗan wuta zai cika ne da aikin ‘yan wuta, ko ma wane irin aiki ya aikata (a baya).” Sannan sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi damƙa da hannunsa ya ce: “Allah mai girma da buwaya ya gama komai game da bayinsa.” Sannan sai ya watsa damƙar hannunsa na dama ya ce: “Wata ƙungiyar tana cikin Aljanna.” Ya kuma watsa na hagu ya ce: “Wata ƙungiya kuma tana cikin wuta.” [Ahmad #6563 da Tirmizi #2141].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa dukkan al'amuran bayi suna hannunsa; da ya ga dama da ya mayar da mutane dukansu sun zama al'umma guda a kan addini ɗaya, watau Musulunci, don ya shigar da su gaba ɗayansu gidan Aljanna. Sai dai hikimarsa ta riga ta hukunta cewa zai shigar da wanda ya ga dama cikin Musulunci don ya shigar da shi gidan Aljanna, su kuma waɗanda suka zalunci kawunansu da kafirci da saɓon Allah, su haɗu da azabarsa, don kuwa ba su da wani majiɓinci da zai jiɓinci al'amuransu ko ya kuɓutar da su daga azabar Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah shi ne abin jiɓintar bawa, ya kuma bauta masa shi kaɗai ba tare da ya haɗa shi da abokin tarayya ba. Allah kuma shi zai jiɓinci lamuran bawansa mumini, ya kula da shi ya ba shi shiriya, ya fitar da shi daga duffan ɓata zuwa ga hasken shiriya, ya kare shi daga duk abin da zai cutar da shi.

2. Alƙur'ani da sunnar Annabi (ﷺ) su ne madogarar Musulmi a kan dukkanin al'amuransu na addini ko na rayuwa, musamman lokacin da suka sami saɓani a tsakaninsu.

3. Kamar yadda Musulmi ya yarda da cewa Allah ne kaɗai mahalicci mai arzutawa mai gudanar da al'amuran halitta, to dole ne ya yarda da cewa shi ne mai yin hukunci tsakanin bayinsa da shari'arsa cikin dukkan al'amuransu.

4. Dogaro ga Allah da komawa gare shi da bauta da tuba, abubuwa ne da suke nuna kamalar bawa.

Suratus Shura (9-12)

وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَهُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَلَٰكِن يُدۡخِلُ مَن يَشَآءُ فِي رَحۡمَتِهِۦۚ وَٱلظَّٰلِمُونَ مَا لَهُم مِّن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٍ ٨ أَمِ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَۖ
فَٱللَّهُ هُوَ ٱلۡوَلِيُّ وَهُوَ يُحۡيِ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٩ وَمَا ٱخۡتَلَفۡتُمۡ فِيهِ مِن شَيۡءٖ فَحُكۡمُهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبِّي عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُ
وَإِلَيۡهِ أُنِيبُ ١٠ فَاطِرُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ جَعَلَ لَكُم مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ أَزۡوَٰجٗا وَمِنَ ٱلۡأَنۡعَٰمِ أَزۡوَٰجٗا يَذۡرَؤُكُمۡ فِيهِۚ لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٞۖ وَهُوَ
ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ١١ لَهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقۡدِرُۚ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١٢

9. Ko dai sun riƙi wasu majiɓinta ne ba Shi ba. To Allah Shi ne Majiɓinci, Shi ne kuma Yake raya matattu, Shi kuma Mai iko ne a kan komai.

10. Kuma duk wani abu da kuka yi saɓani a kansa, to sai ku mai da hukuncinsa ga Allah. Wannan Shi ne Allah Ubangijina, gare Shi kawai na dogara, kuma wurinsa kawai nake mayar da al'amarina.

11. (Shi ne) Mahaliccin sammai da ƙasa. Ya halitta muku mataye daga jinsinku, daga dabbobi ma (Ya halicce su) maza da mata; Yana yaɗa ku ta hanyarsa (haɗin jinsin biyu). Babu wani abu da ya yi kama da Shi; kuma Shi Mai ji ne, Mai gani.

12. Mabuɗan taskokin sammai da ƙasa nasa ne; Yana shimfiɗa arziki ga wanda Ya ga dama, yana kuma ƙuntatawa. Lalle shi Masanin komai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa mushirikai sun rungumi wasu gumaka suna bautar su ba Allah ba, alhali kuwa Allah shi ne abin bauta na gaskiya; duk wani abin bauta na daban

to ba zai amfanar ko ya cutar ba. Allah ne kuma mai raya matattu domin yi musu hisabi da sakamako, shi ne kuma mai iko a kan komai, don haka shi kaɗai ya cancanci a bautawa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya umarci muminai da cewa duk wani abu da za su yi saɓani a kansa wanda ya danganci shika-shikan addini ko rassansa, to su mayar da hukuncinsa ga Allah, watau su koma zuwa ga littafinsa Alƙur'ani da sunnar Manzonsa (ﷺ). Kuma Manzon Allah (ﷺ) ya tabbatar musu cewa, wanda ya siffantu da waɗannan siffofi shi ne kaɗai Ubangijinsa, kuma a gare shi ya dogara cikin dukkan al'amuransa, kuma wurinsa yake komawa ya tuba, domin ya yafe masa laifukansa.
Ya kuma tabbatar musu da cewa, Allah shi ne mahaliccin sammai da ƙasa ba tare da ya kwaikwaya a wurin wani ba, kuma shi ne ya halitta wa mutane matayensu daga jinsinsu, su ma dabbobin ni'ima, raƙuma da shanu da tumakai da awakai, ya halitta musu matansu daga jinsinsu. Yana kuma halittar mutane ta hanyar auratayyar da ya ƙaddara a tsakanin maza da mata. Kuma ya arzuta su da naman ci da nonon sha daga dabbobin na ni'ima. Babu wani abu da ya yi kama da shi daga cikin halittunsa; shi kuma yana jin duk maganganunsu, yana ganin duk ayyukansu, babu abin da yake ɓuya a gare shi, zai kuma yi wa kowa sakayya a kan ayyukansa kyawawa ko munana.
Sannan ya bayyana cewa mabuɗan taskokin sama da na ƙasa duka nasa ne shi kaɗai, yana yalwata arzikinsa ga wanda ya ga dama cikin bayinsa, don ya jarraba shi ya tabbatar cewa zai gode masa ko zai yi butulci. Yana kuma ƙuntata wa wanda ya ga dama, don shi ma ya jarraba shi ya ga shin zai yi haƙuri ko kuma zai yi fushi da Ƙaddarar Allah. Lalle shi Allah masanin komai ne, shi ya fi kowa sanin maslahar halittarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tushen addinin annabawa duka guda ɗaya ne, shi ne bautar Allah Ɗaya da guje wa bautar waninsa.

2. An ambaci manyan manzannin Allah guda biyar a wuri ɗaya, inda aka fara da manzo na farko bayan Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), shi ne Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sannan aka biyunta da Annabin ƙarshe, watau Annabi Muhammadu (ﷺ), sannan aka ambaci sauran ukun a jere, watau Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya taƙaita ambaton waɗannan annabawa biyar kaɗai bai ambaci sauran ba, saboda shi Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne farkon manzon da Allah ya aiko zuwa ga mutane, don haka addininsa shi ne tushen dukkan addinai da Allah ya saukar. Shi kuma Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) addininsa shi ne asalin addinin *'Alhanifiyya'*, watau mai kauce wa duk wata hanyar ɓarna a koma bin hanyar Allah ɗoɗar. Kuma ta hanyar da'awar Annabi Isma'ila (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne addinin ya yaɗu tsakanin Larabawa, don haka suka kasance suna bin wani ɓirɓishi na karantarwarsa, saboda haka ya zama shi ne mafi shaharar addinai a wurin Larabawa. Shi kuma addinin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne ya fi sauran addinan da suka gabace shi faɗaɗa bayanin hukunce-hukunce na shari'a. Shi kuma addinin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne wanda daga shi sai addinin Musulunci, babu wani manzo a tsakaninsu.

4. Muhimmancin haɗin kai a kan addinin gaskiya da haɗarin rarrabuwa.

Suratus Shura (13-14)
۞شَرَعَ لَكُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا وَصَّىٰ بِهِۦ نُوحًا وَٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ وَمَا وَصَّيۡنَا بِهِۦٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَىٰٓۖ أَنۡ أَقِيمُواْ ٱلدِّينَ وَلَا تَتَفَرَّقُواْ فِيهِۚ كَبُرَ عَلَى ٱلۡمُشۡرِكِينَ مَا تَدۡعُوهُمۡ إِلَيۡهِۚ ٱللَّهُ يَجۡتَبِيٓ إِلَيۡهِ مَن يَشَآءُ وَيَهۡدِيٓ إِلَيۡهِ مَن يُنِيبُ ١٣ وَمَا تَفَرَّقُوٓاْ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡعِلۡمُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۚ وَلَوۡلَا كَلِمَةٞ سَبَقَتۡ مِن رَّبِّكَ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى لَّقُضِيَ بَيۡنَهُمۡۚ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ أُورِثُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِنۢ بَعۡدِهِمۡ لَفِي شَكّٖ مِّنۡهُ مُرِيبٖ ١٤

13. Ya shar'anta muku (irin) abin da Ya yi wa Nuhu wahayi da shi na addini, da kuma wanda Muka yiwo maka wahayinsa, da kuma abin da Muka yi wa Ibrahimu da Musa da Isa wasiyya da shi cewa: "Ku tsayar da addini, kuma kada ku rarraba a cikinsa." Abin da kake kiran kafirai zuwa gare shi ya yi musu nauyi. Allah Yana zaɓar wanda Ya ga dama zuwa gare shi (addini) Yana kuma shiryar da wanda Ya mayar da al'amarinsa zuwa gare Shi.

14. Ba su kuma rarrabu ba sai bayan ilimi ya zo musu don zalunci da ke tsakaninsu. Ba don kalmar da ta riga ta gabata daga Ubangijinka ba (ta jinkirta musu) zuwa ga wani lokaci ƙayyadajje, da lalle an yi hukunci tsakaninsu. Kuma lalle waɗanda aka gadar wa da littafi a bayansu lallai suna cikin shakka mai sa kokwanto game da shi (Annabi Muhammadu).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, addinin Musulunci da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi irin addinin da annabawan Allah suka zo da shi ne, domin ya shar'anta wa wannan al'umma irin abin da ya umarci Annabi Nuhu da shi da abin da ya yi wa Manzonsa Muhammadu (ﷺ) wahayinsa da abin da ya umarci Annabi Ibrahimu da Annabi Musa da Annabi Isa su isar da shi su kuma yi aiki da shi. Abin da umarnin ya ƙunsa a dunƙule kuwa shi ne su tsayar da addini su kiyaye koyarwarsa, tushensa da ressansa, kada kuma su rarraba a kansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa abin da yake kiran mushirikai zuwa gare shi na Tauhidi da aiki na ƙwarai da ƙaurace wa bautar wanin Allah ya yi musu girma da wahala sosai, domin suna ganin ba za su iya barin bautar gumakansu su bauta wa Allah Ɗaya ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa shiriya da ɓata duka suna hannunsa, shi ne yake zaɓar wanda ya ga dama daga bayinsa ya shiryar da shi zuwa ga bautarsa da ɗa'arsa, ya kuma shiryar da duk wanda yake komawa gare shi da tuba daga zunubansa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin da ya jawo rarrabuwar mutane bayan ya umarce su da haɗa kansu, da cewa kafirai da mushirikai ba su rarrabu ba sai bayan da hujja ta tabbata a kansu da aiko Annabi (ﷺ) zuwa gare su, kuma sun rarrabu ne saboda zalunci da rashin jituwa a tsakaninsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa ba don ya riga ya zartar a cikin iliminsa cewa ba zai yi musu azaba yanzu ba, zai jinkirta musu har zuwa wani ƙayyadajjen lokaci, shi ne ranar alƙiyama, to da tuni ya yi hukunci a tsakaninsu, ya gaggauto musu da azaba saboda kafircinsu da ƙaryatawarsu ga manzanninsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa Yahudawa da aka ba su Attaura da Nasara da aka ba su Linjila tun bayan wucewar kakanninsu suna nan a kan tababa da shakka game da Alƙur'ani da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi, saboda haka suka ƙaryata shi suka kafirce masa.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin kira zuwa ga Allah.

2. Matakin farko ga mai kira zuwa ga Allah shi ne shi ma ya daidaita a kan tafarki miƙaƙƙe ta hanyar aiki da gaskiyar da yake faɗa wa mutane.

3. Daidaito a kan miƙaƙƙen tafarki yana nufin bin umarnin Allah kai-tsaye da kauce wa haninsa.

4. Abin da zai taimaka wa mai wa'azi ya ci nasara a fagen wa'azinsa, shi ne ya zamanto mai ingantacciyar manufa, mai tsayawa kyam a kan kyakkyawar manufarsa da nisantar bin son zuciya; da tsayar da adalci; da ba da muhimmanci ga abubuwan da aka haɗu a kansu; da guje wa jayayya marar ma'ana; da tunatarwa a kan makoma ta ƙarshe.

5. Rashin adalcin ma’abota littafi game da Manzo (ﷺ) da sukar da suke yi masa, ba za su hana a yi musu adalci a yabi annabawansu da littattafan da Allah ya saukar musu ba, domin mumini dole ne ya yi imani da su baki ɗaya.

6. Duk da kasancewar ayar ta sauka a Makka amma tana ƙunshe da wata mu’ujiza ta bayar da labarin abin da bai faru ba, domin ta nuna Annabi (ﷺ) nan gaba zai yi ƙarfi har Yahudawa su zamanto a ƙarƙashin hukuncinsa, shi kuma ya yi musu hukunci da adalci. Haka kuwa shi ya tabbata bayan Manzon Allah (ﷺ) ya yi hijira, sai ga shi Yahudawa, Banu Kuraiza da Banun Nadir da Banu Kainuƙa sun dawo ƙarƙashinsa, kuma yana yi musu hukunci na adalci.

Suratus Shura (15)
فَلِذَٰلِكَ فَٱدۡعُۖ وَٱسۡتَقِمۡ كَمَآ أُمِرۡتَۖ وَلَا تَتَّبِعۡ أَهۡوَآءَهُمۡۖ وَقُلۡ ءَامَنتُ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِن كِتَٰبٖۖ وَأُمِرۡتُ لِأَعۡدِلَ بَيۡنَكُمُۖ ٱللَّهُ رَبُّنَا وَرَبُّكُمۡۖ لَنَآ أَعۡمَٰلُنَا وَلَكُمۡ أَعۡمَٰلُكُمۡۖ لَا حُجَّةَ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمُۖ ٱللَّهُ يَجۡمَعُ بَيۡنَنَاۖ وَإِلَيۡهِ ٱلۡمَصِيرُ ١٥

15. Saboda wannan sai ka yi kira (zuwa ga addinin Allah), kuma ka tsaya kyam kamar yadda aka umarce ka, kada ka bi son ransu; ka kuma ce: “Na yi imani da abin da Allah Ya saukar na littattafai; an kuma umarce ni da yin adalci a tsakaninku; Allah ne Ubangijinmu kuma Ubangijinku; (sakamakon) ayyukanmu namu ne, ku ma (sakamakon) ayyukanku naku ne; babu wata jayayya a tsakaninmu da ku; Allah zai tara mu; kuma zuwa gare Shi ne kaɗai makoma.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi kira zuwa ga bin miƙaƙƙen addini, ya kuma tsaya kyam a kansa kamar yadda Allah ya umarce shi, kada ya bi soye-soyen zukatan kafirai. Idan kuma suna jayayya da shi ne to ya faɗa musu cewa, shi ya yi imani da Allah ya kuma yi imani da littattafan da ya saukar wa manzanninsa, kuma Allah ya umarce shi da ya yi musu hukunci da adalci. Ya kuma tabbatar musu cewa wanda yake bauta wa shi ne Ubangijinsu baki ɗaya, kuma su sani cewa, kowa yana tare da sakamakon ayyukansa kyawawa ko munana, babu wata sauran jayayya a tsakaninsu bayan hujja ta riga ta bayyana a fili, hanyar gaskiya kuma ta fito sarari. Allah ne kuma zai haɗa su baki ɗaya a ranar alƙiyama, domin zuwa gare shi makomar kowa take, inda zai yi wa kowa sakayya gwargwadon irin aikinsa na alheri ko na sharri, a gane mai gaskiya da maƙaryaci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk masu jayayya a kan addinin Allah ko wasu tabbatattun hukunce-hukuncensa suna sukan su, ba su da wata hujja sai tsabar son zuciya da butulce wa Allah.

2. Duk wani mai son Musulmi su koma rayuwa irin ta jahiliyya bayan suna Musulmi, to lalle wannan yana cikin masu jayayya a kan addinin Allah. Hakanan duk masu ƙoƙarin sanya wa Musulmi shakka game da nagartar addininsu da koyarwarsa to shi ma ya shiga ƙarƙashin wannan ayar.

3. Annabi (ﷺ) bai san gaibu ba, musamman game da lokacin zuwan alƙiyama.

4. Bayanin kusantowar ranar alƙiyama.

5. Tsoron ranar alƙiyama yana taimaka wa mumini wajen tashi tsaye domin yi mata tanadi.

Suratus Shura (16-18)

وَٱلَّذِينَ يُحَآجُّونَ فِي ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا ٱسۡتُجِيبَ لَهُۥ حُجَّتُهُمۡ دَاحِضَةٌ عِندَ رَبِّهِمۡ وَعَلَيۡهِمۡ غَضَبٞ وَلَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٌ ١٦ ٱللَّهُ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ وَٱلۡمِيزَانَۗ وَمَا يُدۡرِيكَ لَعَلَّ ٱلسَّاعَةَ قَرِيبٞ ١٧ يَسۡتَعۡجِلُ بِهَا ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِهَاۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مُشۡفِقُونَ مِنۡهَا وَيَعۡلَمُونَ أَنَّهَا ٱلۡحَقُّۗ أَلَآ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُمَارُونَ فِي ٱلسَّاعَةِ لَفِي ضَلَٰلِۭ بَعِيدٍ ١٨

16. Waɗanda kuma suke jayayya game da Allah bayan an amsa masa (kiransa), to hujjarsu ɓatacciya ce a wurin Ubangijinsu, kuma fushi ya hau kansu, kuma suna da azaba mai tsanani.

17. Allah ne Ya saukar da Littafi da gaskiya da kuma adalci. Me yake sanar da kai cewa ko alƙiyama kusa take.

18. Waɗanda ba sa yin imani da ita suna gaggauto da ita; waɗanda kuwa suka yi imani a tsorace suke da ita, kuma suna sane da cewa ita gaskiya ce. Ku saurara, lalle waɗanda suke jayayya game da tashin alƙiyama tabbas suna cikin ɓata mai nisa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda suke dogaro da ɓatacciyar hujja suna jayayya game da addinin Allah, watau Musulunci, bayan kuwa mutane sun amsa kiransa sun shiga addinin Allah ƙungiya-ƙungiya, to masu wannan jayayyar hujjarsu ta banza ce a wurin Allah da sauran muminai; ba ta da wani tasiri na a zo a gani, sannan fushin Allah ya tabbata a kansu saboda kafircinsu da ƙin gaskiyarsu, kuma wata azaba mai tsanani tana nan tana jiran su a ranar alƙiyama.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ingantacciyar hujja da Musulmi yake riƙe da ita, watau Alƙur'ani, da cewa Allah ne wanda ya saukar da Alƙur'ani, babu wata tantama game da shi, ya kuma saukar da adalci domin yi wa mutane hukunci da shi. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa ranar alƙiyama da kafirai suke ƙaryata zuwanta kusa take, domin duk wani abu mai zuwa to kusa yake. To amma duk da haka sai waɗanda ba su yi imani da ita ba su riƙa gaggauto ta, domin ba su ma yarda akwai ta ba balle a yi hisabi da sakamako a cikinta. Amma waɗanda suka yi imani da Allah suna cike da tsoron ta domin idan ta zo suna tsoron makomarsu, amma sun tabbata ba sa kokwanto cewa ita gaskiya ce.
Sannan Allah ya tabbatar da cewa, masu jayayya game da ranar alƙiyama suna ƙaryata zuwanta, ba shakka sun tabbata cikin ɓata mai nisa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin luɗufin Allah ga bayinsa da tausasawarsa gare su.

2. Arziƙi na Allah ne, shi ne yake ba da shi ga wanda ya ga dama gwargwadon hikimarsa.

3. Haɗarin fifita son duniya a kan lahira.

4. Addini na gaskiya shi ne abin da Allah ya shar'anta ya kuma yi izini da a bi shi. Duk abin da Allah bai shar'anta shi ba, to ba zai taɓa zama addini ba ko da kuwa wasu mutane suna ganin mai kyau ne.

5. Haƙƙin shar'antawa da halattawa da haramtawa duka na Allah ne shi kaɗai. Duk wanda ya ba wa kansa wannan haƙƙi ko aka ba shi, to ya zama abokin tarayya ga Allah.

6. Falala mai girma ita ce Allah ya datar da bawansa ga yin imani da aiki nagari wanda zai kai shi ga shiga Aljanna ranar alƙiyama.

Suratus Shura (19-22)

ٱللَّهُ لَطِيفُۢ بِعِبَادِهِۦ يَرۡزُقُ مَن يَشَآءُۖ وَهُوَ ٱلۡقَوِيُّ ٱلۡعَزِيزُ ١٩ مَن كَانَ يُرِيدُ حَرۡثَ ٱلۡأٓخِرَةِ نَزِدۡ لَهُۥ فِي حَرۡثِهِۦۖ وَمَن كَانَ يُرِيدُ حَرۡثَ ٱلدُّنۡيَا نُؤۡتِهِۦ مِنۡهَا وَمَا لَهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِن نَّصِيبٍ ٢٠ أَمۡ لَهُمۡ شُرَكَٰٓؤُاْ شَرَعُواْ لَهُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا لَمۡ يَأۡذَنۢ بِهِ ٱللَّهُۚ وَلَوۡلَا كَلِمَةُ ٱلۡفَصۡلِ لَقُضِيَ بَيۡنَهُمۡۗ وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٢١ تَرَى ٱلظَّٰلِمِينَ مُشۡفِقِينَ مِمَّا كَسَبُواْ وَهُوَ وَاقِعُۢ بِهِمۡۗ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فِي رَوۡضَاتِ ٱلۡجَنَّاتِۖ لَهُم مَّا يَشَآءُونَ عِندَ رَبِّهِمۡۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَضۡلُ ٱلۡكَبِيرُ ٢٢

19. Allah Mai tausasa wa bayinsa ne, Yana arzuta wanda ya ga dama; kuma Shi Kaƙƙarfa ne, Mabuwayi.

20. Wanda ya kasance yana nufin ladan lahira to za Mu ƙara masa a kan ladansa; wanda kuwa ya kasance yana nufin ladan duniya to za Mu ba shi (wani abu) daga gare ta, kuma ba shi da wani rabo a lahira.

21. Ko dai suna da wasu abokan tarayya ne da suka shar'anta musu wani abu na addini wanda Allah bai yi izinin yin sa ba? Ba don kalmar yin hukunci (a lahira) ta tabbata ba, da lalle an yi hukunci a tsakaninsu (tun a duniya). Lalle kuma azzalumai suna da azaba mai raɗaɗi.

22. Za ka ga azzalumai suna tsoron sakamakon abin da suka aikata, alhali kuwa ga shi zai faɗa musu. Waɗanda kuwa suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, to suna cikin dausayoyin gidajen Aljanna; suna samun duk abin da suka ga dama a wurin Ubangijinsu. Wannan ita ce falala mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tausasawarsa ga bayinsa gaba ɗayansu, muminansu da kafiransu, yana yalwata arzikinsa ga wanda ya ga dama, ya ƙuntata wa wanda ya ga dama, duk dai cikin rahamarsa, ko da kuwa wasu a zahiri suna ganin ba haka ba ne, domin shi ne ƙaƙƙarfa wanda babu mai rinjayar sa, mabuwayi mai azabtar da maƙiyansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk wanda ya kasance yana nufin samun ladan lahira da ayyukansa nagari, to zai ninninka masa ladansa, domin duk kyakkyawan aiki ɗaya yana ninninka ladansa har sau goma har zuwa sau ɗari bakwai, har zuwa ninkin-ba-ninkin. Duk kuma wanda ya kasance duniya kaɗai yake nufi da ayyukansa, to shi ma zai ba shi gwargwadon rabonsa a nan duniya, amma kuma a lahira ba shi da sauran wani rabo, domin ya fifita duniya a kan lahira.

An karɓo daga Ubayyu ɗan Ka'ab (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ka yi wa wannan al'umma albishir na haske da ɗaukaka da nasara da kafuwa a bayan ƙasa. Duk wanda daga cikinsu ya yi aikin lahira domin duniya, to ba ya da wani rabo a lahira." [Ahmad #21222 da Ibn Hibban #405].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya karanta faɗar Allah: "Wanda ya kasance yana nufin ladan lahira, to za mu ƙara masa a kan ladansa, wanda kuwa ya kasance yana nufin ladan duniya, to za mu ba shi daga gare ta, kuma ba shi da wani rabo a lahira." Sannan Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah mai girma da buwaya yana cewa: "Ya kai ɗan'adam, ka ba da cikakken lokacinka domin bautata, zan cika maka ƙirjinka da wadata, zan kuma toshe maka talaucinka, idan ba haka ba kuwa zan cika ƙirjinka da shagaltuwa, ba kuma zan toshe talaucinka ba." [Al-Hakim #3657].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi mushirikai da suke ƙaryata Manzonsa suna yin shirka da Allah cewa, shin suna da wasu alloli ne masu tarayya da Allah waɗanda suka shar'anta musu bin wani

addini daban wanda Allah bai yi musu izinin bin sa ba, don haka suke yi masa shirka suke kuma haramta abin da ya halatta ko su halatta abin da ya haramta? Watau haƙiƙa ba abin da suke bi na shari'ar Allah in ban da soye-soyen zukatan shaiɗanunsu na aljanu da mutane masu haramta musu abin da Allah ya halatta, su kuma halatta musu abin da Allah ya haramta, su riƙa ingiza su cikin saɓon Allah da bijire wa bautarsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa ba don ya riga ya sanya wani ƙayyadajjen lokaci na yin hukunci tsakaninsu ba, watau ranar alƙiyama, to da tuni ya zartar musu da hukuncinsa tun a nan duniya. To amma su sani cewa lalle azzalumai waɗanda suka cuci kawunansu da aikata shirka da saɓon Allah suna da azaba mai raɗaɗi da take jiran su ranar alƙiyama.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda azzalumai masu shirka da saɓon Allah da kauce wa dokokinsa za su sami kansu a ranar alƙiyama, ranar da za a gan su cike da tsoron uƙubar da za ta same su saboda laifukansu, kuma ba makawa sai uƙubar ta auka musu, domin tsoronsu ba zai amfane su da komai ba a ranar. To amma waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa suka yi kyawawan ayyuka, to su kam suna cikin lambunan gidajen Aljanna suna morewarsu, duk abin da suka buƙata a wajen Ubangijinsu na dangogin ni'ima za su same shi, ba kuma mai yankewa ba. Wannan ita ce falala mai girma wadda babu irinta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Busharar gidan Aljanna da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi wa bayinsa muminai masu ayyuka nagari ita ce mafi girman bushara da ɗan'adam ya taɓa ji.

2. Ba ya dacewa ga mai kira zuwa ga Allah ya riƙa neman mutane su biya shi ladan isar musu da saƙon Allah.

3. Soyayyar da Kuraishawa za su nuna wa Manzon Allah (ﷺ) ba shi za ta amfana ba, su za ta amfana, domin shi ne yake isar musu da alheri cikin zukatansu, yake ɗora su a kan hanyar shiriya, sannan kuma su sami ladan wannan ƙauna da za su nuna masa a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka ba lada ne suka biya shi ba.

4. Yalwar rahamar Allah ga bayinsa da falalarsa gare su, domin duk wanda ya yi aiki ɗaya kyakkyawa sai Allah ya ninninka masa ladansa ninki mai yawa.

5. Tuhumar Manzon Allah (ﷺ) da yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ƙarya ba ƙaramin laifi ne ga Allah ba, domin masu wannan tuhumar kamar suna cewa ne, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da nasararsa da goyon bayansa ga mutumin da yake yi masa ƙarya yana faɗa wa mutane cewa ana yi masa wahayi, alhalin ƙarya yake, amma duk da haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙarfafar sa da ƙwararan hujjoji da bayyanannun mu'ujizoji, yana ba shi rinjaye a kan abokan gabansa masu ƙoƙarin tozarta shi. Babu shakka faɗin haka babbar suka ce ga Allah Ta'ala. Don haka samun nasarori da Allah ya yi ta ba Annabi (ﷺ) babban dalili ne da yake tabbatar da gaskiyarsa da gaskiyar Alƙur'ani.

Suratus Shura (23-26)

ذَٰلِكَ ٱلَّذِى يُبَشِّرُ ٱللَّهُ عِبَادَهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ ۗ قُل لَّآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ أَجْرًا إِلَّا ٱلْمَوَدَّةَ فِى ٱلْقُرْبَىٰ ۗ وَمَن يَقْتَرِفْ حَسَنَةً نَّزِدْ لَهُۥ فِيهَا حُسْنًا ۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ شَكُورٌ ﴿٢٣﴾ أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا ۖ فَإِن يَشَإِ ٱللَّهُ يَخْتِمْ عَلَىٰ قَلْبِكَ ۗ وَيَمْحُ ٱللَّهُ ٱلْبَٰطِلَ وَيُحِقُّ ٱلْحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦٓ ۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ﴿٢٤﴾ وَهُوَ ٱلَّذِى يَقْبَلُ ٱلتَّوْبَةَ عَنْ عِبَادِهِۦ وَيَعْفُواْ عَنِ ٱلسَّيِّاتِ وَيَعْلَمُ مَا تَفْعَلُونَ ﴿٢٥﴾ وَيَسْتَجِيبُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَيَزِيدُهُم مِّن فَضْلِهِۦ ۚ وَٱلْكَٰفِرُونَ لَهُمْ عَذَابٌ شَدِيدٌ ﴿٢٦﴾

23. Wannan fa shi ne abin da Allah Yake yin albishir da shi ga bayinsa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari. Ka ce: “Ba na tambayar ku wani lada a kansa (isar da saƙon), sai dai kawai soyayya ta zumunta”. Duk wanda ya aikata wani aiki kyakkyawa za Mu ƙara masa kyakkyawan sakamako a kansa. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai godiya.

24. A’a, suna dai cewa ya ƙaga wa Allah ƙarya ne; to da Allah Ya ga dama da sai Ya rufe zuciyarka. Allah kuma Yana shafe ƙarya Yana kuma tabbatar da gaskiya da kalmominsa. Lalle Shi Masanin abubuwan da suke cikin zukata ne.

25. Shi ne kuma wanda Yake karɓar tuba daga bayinsa, Yake kuma yin afuwa game da munanan (ayyuka), Yana kuma sane da abin da kuke aikatawa.

26. Kuma Yana amsa wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, Yana kuma ƙara musu daga falalarsa. Kafirai kuwa suna da azaba mai tsanani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk abubuwan da ya ambata a baya na ni’imomin Aljanna wani babban albishir ne yake yi wa bayinsa waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa, suka kuma yi aiki nagari. Haka kuma ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya shaida wa mushirikan Kuraishawa cewa shi fa ba ya neman wani lada a kan isar musu da saƙo na gaskiya, in ban da abu ɗaya wanda kuma su zai amfana, watau su ƙaunace shi saboda kusancin zumunta da ke tsakaninsa da su.

An tambayi Abdullahi ɗan Abbas dangane da wannan, sai Sa’idu ɗan Jubair ya ce: “Ana nufin makusanta na iyalan Muhammadu (ﷺ).” Sai Ibn Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce masa: “Ka yi garaje, yadda abin yake, shi Annabi (ﷺ) babu wani gida daga gidajen Kuraishawa face yana da dangantaka ta zumunci da shi, shi ne ya ce: “Sai dai ku sadar da zumuncin da ke tsakanina da ku.” [Bukhari #4818].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk wanda ya yi kyakkyawan aiki to zai ninninka masa ladansa, duk kyakkyawan aiki ɗaya kuma zai ninka masa shi goma har fiye da haka. Allah kuma tabbas mai yawan gafarta zunuban bayinsa ne masu tuba, kuma mai yawan godiya ne a kan kyawawan ayyukan da suka yi dominsa.
Yana daga cikin ƙarairayin kafirai da suke cewa Annabi Muhammadu (ﷺ) shi ne ya ƙirƙiri Alƙur’ani ba wahayinsa Allah ya yi masa ba. To Allah ya ƙaryata su ya kuma mayar musu da martani a kan haka da cewa, da a ce zuciyarsa za ta riya masa cewa ya ƙirƙiri Alƙur’ani da kansa ya jingina wa Allah, to lalle da Allah ya toshe masa zuciyarsa yadda ba zai iya ƙara fahimtar komai ba, kuma duk wani alheri ya ƙi shiga cikinta; da kuma ya shafe wannan ƙaryar da zai ƙirƙira ya wanzar da gaskiya. To tunda hakan bai faru ba, wannan ya nuna Annabi (ﷺ) gaskiya yake faɗa cewa Allah ne yake yi masa wahayin Alƙur’ani. Lalle shi Allah masanin abin da yake cikin zukata ne, babu abin da yake ɓuya a gare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana baiwar da yake yi wa bayinsa idan sun yi laifi sun tuba, da cewa, shi ne yake karɓar tubarsu ya yafe musu munanan laifukansu, yana kuma sane da duk abin da suke aikatawa, zai kuma yi musu sakayya a kai.
Haka kuma yana amsa addu’ar waɗanda suka yi imani da shi da kuma manzanninsa, yana ma ba su har abin da ba su roƙe shi ba daga falalarsa. Su kuma waɗanda suka kafirce wa Allah da manzanninsa suna da wata azaba mai tsanani da take jiran su a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samu da rashi duk suna faruwa ne a kan wata hikima ta Allah wadda ba kowa ne yake gane ta ba.

2. Yawan wadata sau da yawa yakan jawo ɗagawa da zalunci a cikin al’umma.

3. Tunatar da mutane wata babbar ni’ima wadda koyaushe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi musu, wadda take shafar kowa da komai har ma dabbobi da tsuntsaye, watau saukar da ruwan sama daidai gwargwadon buƙata.

Suratus Shura (27-28)

*وَلَوۡ بَسَطَ ٱللَّهُ ٱلرِّزۡقَ لِعِبَادِهِۦ لَبَغَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَٰكِن يُنَزِّلُ بِقَدَرٖ مَّا يَشَآءُۚ إِنَّهُۥ بِعِبَادِهِۦ خَبِيرُۢ بَصِيرٞ ٢٧ وَهُوَ ٱلَّذِي يُنَزِّلُ ٱلۡغَيۡثَ مِنۢ بَعۡدِ مَا قَنَطُواْ وَيَنشُرُ رَحۡمَتَهُۥۚ وَهُوَ ٱلۡوَلِيُّ ٱلۡحَمِيدُ ٢٨

27. Da kuma Allah Ya shimfiɗa wa bayinsa arziki to da sun yi tsaurin kai a bayan ƙasa, sai dai kuma Yana saukarwa ne daidai gwargwado yadda Ya ga dama. Lalle Shi Masani ne game da bayinsa, Mai ganin (ayyukansu).

28. Shi ne kuma Yake saukar da ruwan sama bayan sun ɗebe ƙauna, Ya kuma yaɗa rahamarsa. Kuma Shi ne Majiɓincin al’amura, Sha-yabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimarsa ne wajen raba arzikinsa ga bayinsa yadda zai amfane su, da cewa da zai yalwata wa kowa arziki, ya ba wa kowa fiye da buƙatarsa, to da yin haka ya haifar da ɓarna a bayan ƙasa, domin mutane za su riƙa yi wa junansu ɗagawa da ji-ji-da-kai, babu mai sauraron wani. Sai dai Allah yana saukar da arzikinsa ne daidai gwargwadon yadda zai amfani mutane ba za su lalace ba gaba ɗayansu, ya wadata wanda ya ga dama, ya talauta wanda ya ga talaucin ne ya fi dacewa da shi, domin shi ne mai cikakken sanin halayen bayinsa, mai ganin duk abin da suke ciki, don haka yake gudanar da komai cikin hikima.
Sai kuma ya bayyana arzikin ruwan sama da yake saukar wa bayinsa bayan sun ɗebe ƙauna, sai ya wadata shi ko’ina, ƙasa ta fitar da shuke-shukenta, daga nan rahamar Allah ta wanzu ko’ina. Allah yana yin haka ne domin shi ne majiɓincin al’amuran bayinsa, sha-yabo a cikin kowane yanayi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittar sammai da ƙasa da dukkan halittun da suke cikinsu, wani babban dalili ne mai tabbatar da Uluhiyyar Allah da ikon tayar da halittunsa bayan mutuwarsu don yi musu hisabi.

2. Zunubai da saɓon Allah su ne suke jawo masifu ga ɗan’adam ko ga al’umma.

3. Yalwar rahamar Allah ga bayinsa inda yake yafe musu laifukansu masu yawa ba ya kama su da su.

4. Idan wata masifa ta auku a duniya sakamakon wani mummunan aiki, to hakanan alhairan duniya sukan iya samuwa a sakamakon wani aikin alheri.

5. Gudanar jiragen ruwa a cikin kogi tare da girmansu ba tare da sun nutse ba, wata babbar ayar Allah ce mai nuna girman Kudurarsa da Kaɗaitakarsa.

6. Haƙuri da godiya su ne siffofin masu ɗaukar izina daga ayoyin Allah.

Suratus Shura (29-35)

وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ خَلۡقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَثَّ فِيهِمَا مِن دَآبَّةٖۚ وَهُوَ عَلَىٰ جَمۡعِهِمۡ إِذَا يَشَآءُ قَدِيرٞ ٢٩ وَمَآ أَصَٰبَكُم مِّن مُّصِيبَةٖ فَبِمَا كَسَبَتۡ أَيۡدِيكُمۡ وَيَعۡفُواْ عَن كَثِيرٖ ٣٠ وَمَآ أَنتُم بِمُعۡجِزِينَ فِي ٱلۡأَرۡضِۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٖ ٣١ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِ ٱلۡجَوَارِ فِي ٱلۡبَحۡرِ كَٱلۡأَعۡلَٰمِ ٣٢ إِن يَشَأۡ يُسۡكِنِ ٱلرِّيحَ فَيَظۡلَلۡنَ رَوَاكِدَ عَلَىٰ ظَهۡرِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّكُلِّ صَبَّارٖ شَكُورٍ ٣٣ أَوۡ يُوبِقۡهُنَّ بِمَا كَسَبُواْ وَيَعۡفُ عَن كَثِيرٖ ٣٤ وَيَعۡلَمَ ٱلَّذِينَ يُجَٰدِلُونَ فِيٓ ءَايَٰتِنَا مَا لَهُم مِّن مَّحِيصٖ ٣٥

29. Yana kuma daga cikin ayoyinsa halittar sammai da ƙasa da kuma dabbobin da Ya yaɗa a cikinsu. Kuma shi Mai iko ne a kan Ya tara su idan Ya ga dama.

30. Abin da kuma ya same ku na wata masifa, to saboda abin da hannayenku ne suka tsuwurwurta, Yana kuma yin afuwa ga wasu (laifuka) masu yawa.

31. Kuma ku ba za ku gagara ba a bayan ƙasa; kuma ba ku da wani majiɓinci ko mataimaki in ba Allah ba.

32. Daga cikin ayoyinsa kuma akwai jiragen ruwa masu gudu a cikin kogi kamar duwatsu.

33. Idan da Ya ga dama da sai Ya kwantar da iska sai (jiragen) su zama a tsaye cak a kan (kogin). Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga duk wani mai yawan haƙuri, mai yawan godiya.
34. Ko kuma Ya nutsar da su saboda (munanan ayyukan) da suka aikata. Ko kuma ya yi afuwa ga wasu (laifuka) masu yawa.

35. Kuma waɗanda suke jayayya game da ayoyinmu sun san da cewa ba su da wata matsera.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu hujjoji masu tabbatar da cikar Kudurarsa da yalwar ikonsa. Daga cikinsu akwai halittar sammai da ƙasa da dangogin halittu masu ban mamaki da ya sanya a cikinsu, sannan kuma duk sanda ya ga damar ya tara su don yi musu hisabi da sakamako shi mai iko ne a kan haka, babu abin da zai gagare shi, kamar yadda a karon farko halittarsu ba ta gagare shi ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutane illar saɓon sa inda ya shaida musu cewa, babu wata musifa da za ta same su a kawunansu ko a dukiyoyinsu, sai don sakamakon abin da suka aikata ne na saɓon Allah da rashin bin dokokinsa, kuma ma yana yafe musu wasu laifuka da dama, ba ya kama su da su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutane cewa ba za su gagare shi su tsere masa ba idan ya yi nufin azabtar da su, kuma ba su da wani mai jiɓintar lamarinsu ko mai taimakon su ya kautar musu da azabar Allah in ba shi ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wata babbar aya mai nuna cikar Kudurarsa da Kaɗaitakarsa da gaskiyar alƙawarinsa, su ne samar da jiragen ruwa manya-manya masu kamar duwatsu, suna gudu a cikin kogi maƙare da mutane da kayayyakinsu, daga wani yanki na duniya zuwa wani.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa idan ya ga dama sai ya kwantar da iskar da take tafiyar da su, sai su tsaya cak a cikin kogi ba sa motsi. Lalle game da wannan abu da aka ambata akwai ayoyi masu nuna girman Kudurar Allah ga duk wani mai yawan haƙuri mai yawan godiya a kan ni'imomin Allah.
Ko kuma idan Allah ya ga damar hallakar da su sai ya aiko musu guguwa mai ƙarfi ta hallakar da mutanen cikinsu saboda laifukan da suka aikata, ko kuma idan ya ga dama sai yafe musu wasu laifukan masu yawa ba tare da ya kama su da su ba.
Kuma yana yin haka ne don waɗanda suke jayayya game da ayoyinsa su sani cewa ba su da wata matsera da za su guje wa hallaka idan ya so hallaka su, don haka su tuba su bar bautar wani abu ba Allah ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duniya da abin da yake cikinta na jin daɗi da ƙyale-ƙyale ba komai ba ce a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Mumini da kafiri duka ɗaya suke dangane da jin daɗin duniya, amma yayin da suka koma ga Allah to abin da Allah zai tanadar wa mumini shi ne alheri da jin daɗi na har abada.

3. Wajabcin dogaron bawa ga Ubangijinsa cikin dukkan al'amuransa na duniya da na addini.

4. Masu imani da dogaro ga Allah su ne masu more jin daɗin lahira.

5. Duk wani aiki da bawa zai shiga idan babu dogaro ga Allah a cikinsa, to ba zai taɓa cika ba.

6. Tabbatar da cewa laifuka sun kasu kashi biyu; akwai manyan laifuka (*alkaba'ira*); akwai kuma ƙananan laifuka. Duk wani laifi da Allah ya sanya masa haddi a nan duniya ko ya yi alƙawarin azaba ga mai aikata shi a lahira, ko ya la'anci mai aikata shi ko Manzonsa (ﷺ) ya la'ance shi, ko Allah ya yi fushi da mai yin sa, ko ya saukar da wata azabarsa ga masu yin sa, to duk wannan shi ake kira 'kabira', watau babban laifi.

7. Falalar yin afuwa da gafara ga wanda ya munana, idan akwai maslaha a cikin yi masa afuwar. Domin ramuwa haƙƙi ne na wanda aka munana wa, idan ya ga dama ya yi afuwa, to wannan wani karamci ne daga ɓangarensa.

8. Kamalar 'bawa' tana tattare da bayar da haƙƙin Allah na farilla da ke kansa, kamar salla, da kuma kyautata wa bayin Allah ta hanyar ciyar da dukiya.

9. Muhimmancin shawara a kan muhimman al'amura na addini da rayuwa. Yin shawara sananniyar al'ada ce a wurin mutanen Madina, duk sanda wani muhimmin abu ya taso sukan haɗu su yi shawara a junansu. Ta hanyar shawara ne suka kai ga cim ma matsayar yin imani da kiran Manzon Allah (ﷺ) lokacin da wakilansu suka zo musu da labarin da'awarsa daga Makka.

10. Sahabban Annabi (ﷺ) sukan haɗu don gudanar da shawara cikin dukkan muhimman al'amuransu. Sun yi shawara lokacin shugabantar da Sayyidina Abubakar bayan rasuwar Manzon Allah (ﷺ), kamar yadda suka yi shawara game da yaƙar masu ridda da sauran al'amura masu yawa. Manzon Allah (ﷺ) shi ne babban abin koyinsu a nan, domin shi ko da yaushe mai neman shawararsu ne a kan abubuwa idan sun taso.

Suratus Shura (36-39)

فَمَآ أُوتِيتُم مِّن شَيۡءٖ فَمَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ خَيۡرٞ وَأَبۡقَىٰ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ يَتَوَكَّلُونَ ٣٦ وَٱلَّذِينَ يَجۡتَنِبُونَ كَبَٰٓئِرَ ٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡفَوَٰحِشَ وَإِذَا مَا غَضِبُواْ هُمۡ يَغۡفِرُونَ ٣٧ وَٱلَّذِينَ ٱسۡتَجَابُواْ لِرَبِّهِمۡ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَمۡرُهُمۡ شُورَىٰ بَيۡنَهُمۡ وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ٣٨ وَٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَابَهُمُ ٱلۡبَغۡيُ هُمۡ يَنتَصِرُونَ ٣٩

36. Sannan duk wani abu da aka ba ku to jin daɗin rayuwar duniya ne; kuma abin da yake wurin Allah shi ya fi alheri ya kuma fi wanzuwa ga waɗanda suka yi imani suke kuma dogara ga Ubangijinsu.

37. Waɗanda kuma suke nesantar manyan zunubai da munanansu, idan kuma sun yi fushi sukan yafe.

38. (Su ne) kuma waɗanda suka amsa kiran Ubangijinsu suka kuma tsai da salla, al'amarinsu kuwa (suna) shawara ne a tsakaninsu, suna kuma ciyarwa daga abin da Muka arzuta su.

39. (Su ne) kuma waɗanda idan wani zalunci ya shafe su sukan rama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa bayinsa cewa, duniya ba a bakin komai take ba; duk wata dukiya da aka ba su ko mulki ko 'ya'ya ko matsayi, to ɗan jin daɗin rayuwar duniya ne kawai mai gushewa ne babu makawa, jin daɗi na har abada shi ne ni'imar Aljanna wadda Allah ya tanadar wa bayinsa waɗanda suka siffantu da siffofi kamar haka:
Na ɗaya: Waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa.
Na biyu: Waɗanda suke dogara ga Ubangijinsu shi kaɗai cikin dukkan al'amuransu.
Na uku: Su ne waɗanda suke nesantar manyan zunubai, kamar shirka da kisa da sata da cin dukiyar riba da shan giya.
Na huɗu: Suke nesantar munanan ayyuka na alfasha, kamar zina da luwaɗi da maɗigo.
Na biyar: Su ne waɗanda idan an fusata su da wata magana ko da wani aiki, to suna yafe wa wanda ya munana musu ba sa ramuwa.
Na shida: Su ne waɗanda suka amsa kiran Ubangijinsu, suka aikata umarninsa, suka guje wa haninsa.
Na bakwai: Su ne waɗanda suka tsayar da salla yadda ya kamata tare da lura da lokatanta da farillanta da sunnoninta.
Na takwas: Su ne masu yin shawara a tsakaninsu wajen gudanar da al'amuransu, musamman waɗanda suka shafi al'umma, kamar batun yaƙi da na zaman lafiya da tattalin arziki.
Na tara: Su ne masu ciyar da abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya arzuta su da shi don neman yardarsa.
Na goma: Su ne waɗanda idan aka zalunce su suna ɗaukar fansa domin kare mutuncinsu da darajarsu, yayin da azzalumin ya kasance ba wanda ya cancanci a yi masa afuwa ba ne, kuma babu maslaha a cikin yi masa afuwar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halaccin rama mugunta da mugunta kwatankwacinta, amma afuwa ce ta fi alheri.2. Rabuwar mutane kashi uku dangane da rama mugunta:
Na farko: Wanda zai rama fiye da yadda aka yi masa, wannan shi ne azzalumi.
Na biyu: Wanda zai rama kwatankwacin yadda aka yi masa, wannan shi ne adali.
Na uku: Wanda zai yi afuwa ya bar haƙƙinsa, wannan shi ne mai kyautatawa.
Ayar ta ƙunshi duka kashe-kashen guda uku.
Haƙuri da yafiya abubuwa ne da ba kowa yake iya yin su ba sai mutane masu himma da babban rabo.

Suratus Shura (40-43)
وَجَزَٰٓؤُاْ سَيِّئَةٖ سَيِّئَةٞ مِّثۡلُهَاۖ فَمَنۡ عَفَا وَأَصۡلَحَ فَأَجۡرُهُۥ عَلَى ٱللَّهِۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٠ وَلَمَنِ ٱنتَصَرَ بَعۡدَ ظُلۡمِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَا عَلَيۡهِم مِّن سَبِيلٍ ٤١ إِنَّمَا ٱلسَّبِيلُ عَلَى ٱلَّذِينَ يَظۡلِمُونَ ٱلنَّاسَ وَيَبۡغُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٤٢ وَلَمَن صَبَرَ وَغَفَرَ إِنَّ ذَٰلِكَ لَمِنۡ عَزۡمِ ٱلۡأُمُورِ ٤٣

40. Kuma sakamakon mummunan (abu) shi ne mayar da mummuna kamarsa; to wanda ya yi afuwa ya kuma kyautata, to ladansa yana wurin Allah. Lalle Shi ba Ya son azzalumai.

41. Tabbas kuma duk wanda ya rama bayan an zalunce shi, to waɗannan ba wani laifi a kansu.

42. Laifi kam yana kan waɗanda suke zaluntar mutane ne suke kuma yin ta’adda a bayan ƙasa ba da wata hujja ba. Waɗannan suna da azaba mai raɗaɗi.

43. Tabbas kuma wanda ya yi haƙuri ya yafe, to tabbas wannan yana daga muhimman al’amura.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa ya halatta ga duk wanda aka cuta ya nemi haƙƙinsa, amma gwargwadon yadda aka yi masa ba tare da ƙari ko wuce iyaka ba. Sai dai ya sani cewa duk wanda ya yafe cutar da aka yi masa ya kuma kyautata alaƙa tsakaninsa da wanda ya cuce shi, to ladansa yana wurin Allah, shi ne zai biya shi daga taskarsa. Idan kuwa har ya yi zalunci wajen ramuwa, to ya sani lalle Allah ba ya son azzalumai.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar da cewa waɗanda suka rama zaluncin da aka yi musu ba tare da sun ƙetare iyaka ba, to waɗannan babu wani laifi a kansu.An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Masu zagin junansu, laifin abin da suka furta (na zagi) yana kan wanda ya fara, matuƙar wanda aka zalunta bai wuce iyaka ba.” [Muslim #2587].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa laifi da uƙuba sun tabbata ne a kan waɗanda suke zaluntar mutane, suke kuma aikata laifukan saɓon Allah a bayan ƙasa, to waɗannan suna da azaba mai raɗaɗi a ranar alƙiyama.
Amma kuma ya bayyana cewa wanda ya yi haƙuri a kan cutarwar da wani ya yi masa ya yafe masa, to wannan haƙurin nasa zai zame masa alheri har ma da al’ummarsa gaba ɗaya, domin abu ne mai kyau da ba kowa ke iya yin sa ba sai mai babban rabo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shiriya da ɓata na Allah ne, duk wanda ya ɓatar saboda yawan kafircinsa, to babu mai iya shiryar da shi in ba Allah ba.

2. Tsananin azabar lahira zai sanya kafirai su riƙa burin ina ma a sake dawo da su duniya, don su yi imani su yi aiki nagari.

3. Mummunar asara ita ce ta lahira lokacin da kafiri zai rasa gidan Aljanna, ya kuma rasa iyalansa gaba ɗaya.

4. A lahira kafirai ba su da wanda zai taimake su ko ya cece su daga azabar Allah.

Suratus Shura (44-46)
وَمَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن وَلِيّٖ مِّنۢ بَعۡدِهِۦۗ وَتَرَى ٱلظَّٰلِمِينَ لَمَّا رَأَوُاْ ٱلۡعَذَابَ يَقُولُونَ هَلۡ إِلَىٰ مَرَدّٖ مِّن سَبِيلٖ ٤٤ وَتَرَىٰهُمۡ يُعۡرَضُونَ عَلَيۡهَا خَٰشِعِينَ مِنَ ٱلذُّلِّ يَنظُرُونَ مِن طَرۡفٍ خَفِيّٖۗ وَقَالَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ وَأَهۡلِيهِمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ أَلَآ إِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ فِي عَذَابٖ مُّقِيمٖ ٤٥ وَمَا كَانَ لَهُم مِّنۡ أَوۡلِيَآءَ يَنصُرُونَهُم مِّن دُونِ ٱللَّهِۗ وَمَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن سَبِيلٍ ٤٦

44. Wanda kuma Allah Ya ɓatar, to ba shi da wani majiɓinci bayanSa. Kuma za ka ga azzalumai lokacin da suka ga azabar suna cewa: “Ina ma da akwai wata damar komawa (duniya)?”

45. Kuma za ka gan su ana bijiro su a kanta (wutar) suna masu ƙanƙan da kai na wulaƙanci, suna kallo a sace. Waɗanda kuma suka yi imani suka ce: “Lalle asararru su ne waɗanda suka yi asarar rayuwarsu da ta iyalinsu a ranar alƙiyama.” Ku saurara, lalle azzalumai suna cikin azaba dawwamammiya.

46. Kuma ba su da wasu majiɓinta da za su taimake su in ban da Allah. Duk wanda Allah Ya ɓatar, to ba shi da wata hanya daban (ta shiriya).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wanda ya nufe shi da ɓata ya hana shi bin gaskiya saboda mugun halinsa, to ba zai taɓa samun wanda zai jiɓinci al’amarinsa ya shiryar da shi in ba Allah ba.
Sai kuma Allah ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, a ranar alƙiyama zai ga azzalumai waɗanda suka cuci kawunansu da kafirci da saɓon Allah yayin da za su ga azabar wuta da idanunsu, za su riƙa burin ina ma suna da wata damar komawa duniya domin su tuba su gyara halayensu. To amma ina, bakin alƙalami ya riga ya bushe.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya shaida masa cewa, a ranar zai ga waɗannan azzalumai lokacin da ake gindaya su a kan wuta, suna wulaƙantattu ƙaskantattu, suna kallon mutane a sace saboda tsananin tsoro da ya cika musu zuciya, kuma dai abin da suke tsoro ɗin sai ya auka musu ba makawa. A ranar muminai waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa za su ce: Lalle asararru na haƙiƙa su ne waɗanda suka yi asarar kawunansu da iyalansu a ranar alƙiyama saboda azabar da suka haɗu da ita. Lalle azzalumai suna cikin azaba madawwamiya wadda ba za ta yanke ba har abada.
Kuma ba su da waɗanda za su taimaka musu su kuɓutar da su daga azabar Allah a wannan ranar. Duk kuma wanda Allah ya ɓatar da shi saboda mugun halinsa, to ba shi da wata hanya da za ta kai shi zuwa shiriya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin yin gaggawa zuwa ga aikata umarnin Allah da nesantar haninsa.

2. Aikin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗora wa Manzonsa (ﷺ) shi ne isar da saƙo zuwa ga mutane. Bai umarce shi da ya yi gadin su ba.

3. Haramcin yi wa Allah butulci da fushi da ƙaddararsa.

4. `Ya`ya mata ko maza kyauta ce daga Allah, wajibi ne a kan wanda Allah ya arzuta shi da su ya yi masa godiya, ya kuma ɗora su a kan tafarkinsa.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna darajar `ya mace, don haka ya fara ambaton ta kafin ya ambaci namiji, domin wannan ya zama martani ga mushirikan Larabawa masu ƙaskanta `ya`ya mata har sukan kai ga kashe su.

6. Kyautar `ya`ya mata zalla ko maza zalla ko ya haɗa duka biyu ga mutum, duka wannan yana gudana ne daidai da hikimar Allah da iliminsa na sanin abin da ya fi zama maslaha ga bayinsa.

Suratus Shura (47-50)
ٱسۡتَجِيبُواْ لِرَبِّكُم مِّن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَ يَوۡمٞ لَّا مَرَدَّ لَهُۥ مِنَ ٱللَّهِۚ مَا لَكُم مِّن مَّلۡجَإٖ يَوۡمَئِذٖ وَمَا لَكُم مِّن نَّكِيرٖ ٤٧ فَإِنۡ أَعۡرَضُواْ فَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ
عَلَيۡهِمۡ حَفِيظًاۖ إِنۡ عَلَيۡكَ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُۗ وَإِنَّآ إِذَآ أَذَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ مِنَّا رَحۡمَةٗ فَرِحَ بِهَاۖ وَإِن تُصِبۡهُمۡ سَيِّئَةُۢ بِمَا قَدَّمَتۡ أَيۡدِيهِمۡ فَإِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ كَفُورٞ ٤٨

لِلَّهِ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ يَهَبُ لِمَن يَشَآءُ إِنَٰثٗا وَيَهَبُ لِمَن يَشَآءُ ٱلذُّكُورَ ٤٩ أَوۡ يُزَوِّجُهُمۡ ذُكۡرَانٗا وَإِنَٰثٗاۖ وَيَجۡعَلُ مَن يَشَآءُ عَقِيمًاۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٞ قَدِيرٞ ٥٠

47. Ku amsa kiran Ubangijinku tun kafin ranar da ba ta da wata makauta ta zo daga Allah. Ba ku da wata mafaka a wannan ranar, kuma ba ku da damar yin musu.

48. To idan sun bijire, to ba Mu aika ka don ka zama mai gadin su ba; ba abin da yake kanka sai isar da saƙo. Lalle kuma Mu idan Muka ɗanɗana wa mutum wata rahama daga gare Mu sai ya riƙa tutiya da ita. Idan kuma wani mummunan abu ya same su saboda abin da hannayensu suka aikata, to lalle shi mutum butulu ne.

49. Mulkin sammai da ƙasa na Allah ne. Yana halittar abin da Ya ga dama. Yana ba da `ya`ya mata ga wanda Ya ga dama, Yana kuma ba da `ya`ya maza ga wanda Ya ga dama.

50. Ko kuma ya haɗa musu maza da mata; Yakan kuma mayar da wanda ya ga dama bakarare. Lalle Shi Masani ne, Mai iko.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana kiran bayinsa ne da su gaggauta amsa kiransa, su yi aiki da umarninsa su guji haninsa, su daina ɓata wa kansu lokaci, tun kafin zuwan ranar alƙiyama wadda babu wanda ya isa ya hana zuwanta. Kuma ya shaida musu cewa a ranar ba su da wata mafakar da za ta ɓoye su daga Allah, kuma ba su da damar musanta zunuban da suka aikata a duniya. Domin idan ma sun yi musu gaɓoɓinsu ne za su ba da shaida a kansu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa, idan kafirai suka bijire masa suka ƙi amsa kiransa na yin imani da Allah da Manzonsa, to yana tabbatar masa da cewa bai aiko shi don ya zama mai gadin su ba yana kula da ayyukansu; abin da kawai yake kansa shi ne isar da saƙon Allah zuwa gare su, amma hisabinsu yana wurin Allah.
Sai kuma Allah ya bayyana wani mummunan hali na ɗan’adam, watau duk sanda Allah ya ɗanɗana masa wata rahamarsa ta wadata ko lafiya da makamantansu sai ya riƙa fariya da ita yana girman kai; idan kuma ya saukar masa wani bala’i saboda laifin da ya aikata, to sai ya zamanto mai butulce wa ni’imomin Allah mai rashin godiya, ko mai fushi da ƙaddarar Allah da rashin dangana.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikakken mulkinsa da kamalar Kudurarsa, da cewa mulkin sammai da ƙasa duk nasa ne babu mai tarayya da shi a cikinsu; yana halittar abin da ya ga dama a sanda ya ga dama, namiji ko mace ko waninsu; idan ya ga dama ya ba wa wani ‘ya’ya mata zalla ya hana shi maza, wani kuma ya ba shi maza zalla ya hana shi mata, ko kuma ya haɗa wa wanda ya ga dama ‘ya’ya maza da mata, sannan ya mayar da wani bakarare ba ya haihuwa, domin shi masani ne na duk abin da ya wakana da wanda ma zai wakana nan gaba, mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa annabawansa wahayi ta hanyoyi daban-daban.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya magana da kowa sai da zaɓaɓɓun bayinsa, su ne annabawa da manzanni.

3. Alƙur’ani Ruhi ne wanda shi ne yake raya zukata, kuma rayuwar ɗan’adam ba za ta tafi daidai ba sai da aiki da dokokinsa. Duk wanda ya riƙe koyarwar Alƙur’ani shi ne rayayye, wanda kuma ya yi watsi da shi ko ya ƙaryata shi, to shi matacce ne. Al’umma ba za ta rayu ba sai da bin dokokinsa.

4. Annabi Muhammadu (ﷺ) kafin a yo masa wahayi bai san komai ba dangane da littattafan annabawan da suka gabace shi, hasali ma ba ya rubutu ba ya karatu. Wannan shi yake ƙara tabbatar da gaskiyar manzancinsa da cewa wahayi Allah ya yi masa na duk abin da yake karanta wa mutane.

5. Alƙur’ani haske ne, da shi ne muminai suke fita daga duhun kafirci da na ɓata da na jahilci da bidi’o’i.

Suratus Shura (51-53)

*وَمَا كَانَ لِبَشَرٍ أَن يُكَلِّمَهُ ٱللَّهُ إِلَّا وَحۡيًا أَوۡ مِن وَرَآيِٕ حِجَابٍ أَوۡ يُرۡسِلَ رَسُولٗا فَيُوحِيَ بِإِذۡنِهِۦ مَا يَشَآءُۚ إِنَّهُۥ عَلِيٌّ حَكِيمٞ ٥١ وَكَذَٰلِكَ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ رُوحٗا مِّنۡ أَمۡرِنَاۚ مَا كُنتَ تَدۡرِي مَا ٱلۡكِتَٰبُ وَلَا ٱلۡإِيمَٰنُ وَلَٰكِن جَعَلۡنَٰهُ نُورٗا نَّهۡدِي بِهِۦ مَن نَّشَآءُ مِنۡ عِبَادِنَاۚ وَإِنَّكَ لَتَهۡدِيٓ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٥٢ صِرَٰطِ ٱللَّهِ ٱلَّذِي لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ أَلَآ إِلَى ٱللَّهِ تَصِيرُ ٱلۡأُمُورُ ٥٣

51. Kuma zai yiwu ga wani mutum a ce Allah Ya yi magana da shi ba (baki da baki), sai dai wahayi ko kuma ta bayan wani shamaki, ko kuwa Ya aiko wani manzo (mala’ika) sai ya yi masa wahayin abin da ya ga dama da yardarsa. Lalle Shi Maɗaukaki ne, Mai hikima.

52. Kuma kamar haka ne Muka yiwo maka wahayin Ruhi (watau Alƙur'ani) daga umarninmu. Ba ka zamanto ka san mene ne littafi ko kuma imani ba, sai dai kuma Mun sanya shi (Alƙur’ani) haske ne da Muke shiryar da wanda Muka ga dama daga bayinmu da shi. Lalle kuma kai tabbas kana shiryarwa zuwa ga tafarki madaidaici.

53. (Watau) tafarkin Allah wanda Yake da mulkin abin da yake cikin sammai da abin da yake ƙasa. Ku saurara, zuwa ga Allah ne kawai al’amura suke komawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hanyoyin da yake magana da manzanninsa da annabawansa, da cewa ba zai yiwu Allah ya yi magana da wani mutum ba sai ta ɗaya daga cikin hanyoyi uku:
Na farko: Ta hanyar wahayin ilhama ko waninsa, watau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kimsa masa maganarsa a zuciyarsa ba tare da ya yi magana da shi ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle Ruhi mai amana (watau Jibrilu) ya yi mini busa a zuciyata cewa, babu wani rai da zai mutu har sai ya cinye arzikinsa…” [Ibn Abi Shaiba, *Almusannaf* #34332].
Na biyu: Ya yi magana da shi ta bayan wani shamaki inda zai riƙa jin maganarsa amma ba ya ganin sa, kamar yadda ya yi magana da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Na uku: Ya yi masa magana ta hanyar mala’ika, kamar Mala’ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), sai ya sanar da shi abin da Allah ya yi masa izinin ya sanar da shi.
Lalle Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) Maɗaukaki ne a Zatinsa da siffofinsa da ayyukansa; mai hikima ne cikin halittunsa da tsare-tsarensa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda ya yi wa annabawan da suka gabata wahayi, to hakanan ya yi wa Annabi (ﷺ) wahayi wanda gabaninsa bai san wasu littattafai da aka saukar wa manzanni ba, bai kuma san mene ne imani ba, sai ɗai Allah ya saukar masa Alƙur’ani don ya zama haske da shiriya da yake shiryar da waɗanda ya ga dama daga bayinsa zuwa miƙaƙƙen tafarki, watau Musulunci.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Musulunci shi ne hanyar Allah mamallakin abin da yake cikin sammai da abin da yake ƙasa, halittarsa ne, bayinsa ne, kuma shi ne mai gudanar da su. Kuma ya tabbatar da cewa, makomar al'amura duka zuwa gare shi ne, domin ya yi sakayya a kan kowane aiki mai kyau ko mummuna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman darajar Alƙur'ani.

2. Alƙur'ani Balaraben littafi ne, don haka babu mai iya fahimtar sa sai wanda yake fahimtar harshen Larabci. Wannan yana nuna muhimmancin koyon harshen Larabci ga duk wani Musulmi don ya fahimci saƙon Allah.

3. Babu wani bayani da Alƙur'ani ya zo da shi wanda ya ci karo da hankali ko ya saɓa masa, sai dai abin da zai ɗimauta hankulan wasu, wasu kuma za su hankalce shi.

4. Alƙur'ani ya yi bayanin duk abin da ɗan'adam zai buƙata na rayuwar duniya da ta addini da ta lahira.

5. Alƙur'ani littafi ne da yake cike da hikima game da hukunce-hukuncensa da labarunsa da wa'azuzzukansa.

6. Bijirewar mutane daga sauraron gaskiya da karɓar ta ba zai sa a daina faɗa musu ita ba.

43-Suratuz Zukhruf

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Yawancin malaman tafsiri da na hadisi sun kira wannan Sura da '***Suratuz Zukhruf***' saboda zuwan kalmar *'zukhruf*' a cikinta a aya ta 35.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin dukkan malamai, watau ta sauka gabanin hijirar Manzon Allah (ﷺ) zuwa Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta sittin da biyu (62) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratu Fussilat*' kafin '*Suratud Dukhan*'.

4. Adadin ayoyinta:
A wurin yawancin malaman lissafin ayoyin Alƙur'ani ayoyinta tamanin da tara ne (89), amma a lissafin mutanen Sham adadinsu tamanin da takwas ne (88).

5. Babban Jigonta:
Babban jigonta shi ne magana a kan Alƙur'ani mai girma da matsayar kafirai game da shi.
6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin matsayin Alƙur'ani da mu'ujizarsa da tabbatar da gaskiyarsa da gargaɗin masu bijire masa.
• Mamakin halin kafirai na tufka da warwara, watau sun yarda da cewa Allah ne mahaliccin kowa da komai amma kuma suna bauta wa gumaka ba shi ba.
• Jingina wa Allah 'ya'ya mata amma kuma suna yi musu kallon wulaƙanci suna fifita maza a kansu.
• Rushe bautar duk wani abin bauta ba Allah ba komai matsayinsa da martabarsa.
• Tunatar da su labaran al'ummun da suka gabace su da yadda Allah ya hallaka waɗanda suka ƙaryata manzanninsa daga cikinsu, da gargaɗin mushirikan Larabawa da su guje wa aukuwar irin waccan uƙuba a kansu.
• An shigo da dalilai ƙarfafa masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da abokin tarayya ba.

Suratuz Zukhruf (1-8)
حمٓ ١ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ٢ إِنَّا جَعَلۡنَٰهُ قُرۡءَٰنًا عَرَبِيّٗا لَّعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ٣ وَإِنَّهُۥ فِيٓ أُمِّ ٱلۡكِتَٰبِ لَدَيۡنَا لَعَلِيٌّ حَكِيمٌ ٤ أَفَنَضۡرِبُ عَنكُمُ ٱلذِّكۡرَ صَفۡحًا أَن كُنتُمۡ قَوۡمٗا مُّسۡرِفِينَ ٥ وَكَمۡ أَرۡسَلۡنَا مِن نَّبِيّٖ فِي ٱلۡأَوَّلِينَ ٦ وَمَا يَأۡتِيهِم مِّن نَّبِيٍّ إِلَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٧ فَأَهۡلَكۡنَآ أَشَدَّ مِنۡهُم بَطۡشٗا وَمَضَىٰ مَثَلُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٨

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. HA MIM.

2. Na rantse da Littafi mabayyani (Alƙurʾani).

3. Lalle Mu Mun sanya shi ya zamo abin karantawa cikin harshen Larabci domin ku hankalta.

4. Lalle kuma shi (Alƙurʾani) a cikin Littafi Lauhul-Mahafuzu a wurinmu tabbas maɗaukaki ne, mai hikima.

5. Yanzu Ma fasa saukar muku da Alƙurʾani Mu watsar da ku, don kun kasance mutane masu yawan ɓarna?

6. Annabi nawa Muka aika wa mutanen farko?

7. Ba kuma wani annabi da yakan zo musu sai sun kasance suna yi masa izgili.
8. Sai Muka hallakar da waɗanda suka fi su tsananin ƙarfi, kuma bayanin yadda aka hallakar da mutanen farko *ya riga ya shuɗe.*

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da wasu haruffa biyu, kamar yadda ya buɗe surori da dama da irin waɗannan haruffan. [Dubi tafsirinmu na farkon *Suratul Baƙara* don ƙarin bayani].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da littafinsa Alƙurʾani mai bayyana hanyar gaskiya da hukunce-hukuncen shariʾa. Ya kuma saukar da shi ne da harshen Larabci domin Larabawa su fahimci maʾanoninsa da abubuwan da ya ƙunsa na shiriya, su isar da su zuwa ga sauran alʾummu waɗanda ba sa magana da harshen Larabci.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, shi Alƙurʾani ya riga ya tabbata a cikin Lauhul Mahfuzu cewa shi mai maɗaukakiyar daraja ne wanda yake cike da hikima. Watau duk abin da ya ƙunsa gaskiya ne, babu kokwanto a cikinsa, kuma maganar Allah ne, ya san da shi tun fil azal.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ba zai yiwu ya bar mutane hakanan kara zube ba, ba tare da ya aiko musu wani manzo, ko ya saukar musu da wani littafi ba, don kawai sun zama mutane maɓarnata. Don haka kada su yi tsammanin cewa, Allah ba zai saukar da Alƙurʾani ba; tabbas zai saukar musu da shi, ya yi musu bayanin komai filla-filla, wanda ya yi imani don kansa, wanda kuma ya kafirce shi ma don kansa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa aiko da manzanni sunnarsa ce daɗaɗɗiya, domin ya aika annabawa da yawa a cikin alʾummun farko, duk kuwa da kasancewar babu wani annabi da zai zo musu sai sun riƙa yi masa izgili, don nuna bijire wa abin da ya zo musu da shi na gaskiya.
Amma duk da haka sai da Allah ya hallakar da waɗanda suka fi tsananin ƙarfi daga cikin alʾummun nan, don haka hallakar da raunana daga cikinsu ba wani aiki ne da zai gagare shi ba. Kuma bayanin yadda aka hallakar da su ya riga ya shuɗe, watau an yi bayaninsa a sarari a cikin Alƙurʾani, kamar yadda aka hallakar da Adawa da Samudawa da mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanen Madyana na Annabi Shuʾaibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mushirikan Larabawa na farko sun yarda da Tauhidir Rububiyya, watau kaɗaita Allah da ayyukansa, to amma wannan bai shigar da su Musulunci ba, domin ba su yarda su kaɗaita Allah da bauta ba.

2. Tabbatar da tashi bayan mutuwa domin hisabi da sakamako.

3. Muʾujizar Alƙurʾani wanda ya ba da labarin cewa komai dangi biyu ne, tun kafin ilimin kimiyyar zamani ya kai ga gano haka da shekaru ɗaruruwa.

4. Ni'imar ababen hawa da Allah ya hore wa ɗan'adam, saboda haka ya zama wajibi a gare shi ya gode masa a kan wannan ni'imar.

Suratuz Zukhruf (9-14)

وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ خَلَقَهُنَّ ٱلْعَزِيزُ ٱلْعَلِيمُ ۝٩ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ مَهْدًا وَجَعَلَ لَكُمْ فِيهَا سُبُلًا لَّعَلَّكُمْ تَهْتَدُونَ ۝١٠ وَٱلَّذِى نَزَّلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءًۢ بِقَدَرٍ فَأَنشَرْنَا بِهِۦ بَلْدَةً مَّيْتًا ۚ كَذَٰلِكَ تُخْرَجُونَ ۝١١ وَٱلَّذِى خَلَقَ ٱلْأَزْوَٰجَ كُلَّهَا وَجَعَلَ لَكُم مِّنَ ٱلْفُلْكِ وَٱلْأَنْعَٰمِ مَا تَرْكَبُونَ ۝١٢ لِتَسْتَوُۥا۟ عَلَىٰ ظُهُورِهِۦ ثُمَّ تَذْكُرُوا۟ نِعْمَةَ رَبِّكُمْ إِذَا ٱسْتَوَيْتُمْ عَلَيْهِ وَتَقُولُوا۟ سُبْحَٰنَ ٱلَّذِى سَخَّرَ لَنَا هَٰذَا وَمَا كُنَّا لَهُۥ مُقْرِنِينَ ۝١٣ وَإِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا لَمُنقَلِبُونَ ۝١٤

9. Lalle kuma idan ka tambaye su wane ne ya halicci sammai da ƙasa, to tabbas za su ce: "(Allah) ne Mabuwayi, Masani Ya halicce su."

10. Wanda Ya sanya muku ƙasa ta zama shimfiɗa, Ya kuma sanya muku hanyoyi a cikinta don ku gane (inda za ku dosa).
11. Wanda kuma Ya saukar da ruwa daidai gwargwado daga sama sannan Muka raya mataccen gari da shi. Kamar haka ne za a fito da ku (daga ƙabarurruka).

12. Kuma wanda Ya halicci dukkan dangogin abubuwa bibbiyu, Ya kuma sanya muku daga jiragen ruwa da kuma dabbobin ni'ima, abubuwan da kuke hawa.

13. Don ku daidaita a kan bayansu, sannan ku tuna ni'imar Ubangijinku lokacin da kuka daidaita a kansu kuma ku ce: "Tsarki ya tabbata ga wanda Ya hore mana wannan, ba mu zamanto masu ikon sarrafa shi ba.

14. "Kuma lalle zuwa ga Ubangijinmu tabbas za mu koma."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa (ﷺ) labarin wani abin mamaki da takaici na mushirikan Larabawa, da cewa da zai tambaye su wane ne ya halicci sammai da ƙasa, to tabbas za su ce wanda ya halicce su shi ne Allah Mabuwayi kuma masanin komai. To amma abin mamakin shi ne yadda suke yi wa Allah shirka suna bautar wasu gumaka ba shi ba tare da cewa sun san shi ne mahaliccin komai da kowa, sun kuma san gumakan nasu ba za su iya halittar ko da ƙuda ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasu ƙwararan dalilai masu tabbatar da girman Ƙudurarsa da Kaɗaitakarsa, da cewa shi ne ya shimfiɗa ƙasa don ta zama matsuguni ga mutane, domin su gudanar da rayuwarsu a kanta, ya kuma shata musu hanyoyi a cikin duwarwatsu da kwazazzabai domin zirga-zirgarsu, don kuma su riƙa gane inda suke dosa yayin tafiye-tafiyensu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa shi ne wanda ya saukar da ruwa daga sama daidai gwargwadon yadda zai ishi buƙatar mutane da dabbobinsu da shuke-shukensu. Da wannan ruwan ne kuma ya raya mataccen gari wanda ba ya fitar da tsironsa. To kamar yadda ya raya wannan matacciyar ƙasar, haka zai raya matattu domin hisabi da sakamako a ranar alƙiyama.
Allah kuma ya ƙara bayyana girman Ƙudurarsa da cewa shi ne wanda ya halicci kowane abu jinsi bibbiyu, kamar mace da namiji da dare da rana da sanyi da zafi da jinsin tsirrai da dabbobi da sauransu.
Kuma har ila yau ya samar wa mutane abubuwan hawa kamar jiragen ruwa da dabbobi, waɗanda suke amfani da su wajen tafiye-tafiyensu a cikin ruwa ko a kan doron ƙasa.
Allah ya yi wa mutane haka ne domin duk sa'adda suka hau abubuwan hawansu na ruwa ko na tudu ko na sama, suka daidaita a kansu, to sai su tuna ni'imar da ya yi musu da ya hore musu su, su tsarkake shi da bakunansu su yi tasbihi gare shi saboda ya ba su damar sarrafa waɗannan abubuwan hawan yadda suke

buƙata. Ba don ya yi musu wannan tagomashi ba to da ba za su iya sarrafa waɗannan abubuwan hawan ba. Kuma su tabbatar da cewa makomarsu gaba ɗaya zuwa ga Ubangijinsu ne.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance idan ya hau abin hawansa yakan yi kabarbari sau uku, sannan sai ya ce: "Tsarki ya tabbata ga wanda ya hore mana wannan, ba mu zamanto masu ikon sarrafa shi ba. Kuma haƙiƙa lalle zuwa ga Ubangijinmu za mu koma." Sannan sai ya ce: "Ya Allah, ina roƙon ka duk wani alheri da taƙawa a wannan tafiyar tawa, da aikin da za ka yarda da shi. Ya Allah, ka sassauta mana wannan tafiyar tamu, ka naɗe mana nisanta. Ya Allah, kai ne abokin tafiya kuma halifa a cikin iyali. Ya Allah, ina neman tsarinka daga wahalhalun tafiya da rashin kyan gani da mummunar makoma game da dukiya da iyali." Idan kuma yana dawowa sai ya sake faɗar wannan ya ƙara da cewa: "Muna masu mayar da al'amari ga Allah, muna masu tuba, masu bauta, masu godiya ga Ubangijinmu." [Muslim #1342].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yawan butulcin ɗan'adam da kafircinsa, yayin da ya jingina wa mahaliccinsa haihuwa ba tare da wata hujja ba, sai shaci-fadi.

2. Yana daga cikin ƙaga wa Allah ƙarya game da wani yanki na bayinsa, watau abin da mushirikan Larabawa suka riƙa yi na ware wasu dabbobi su ce na Allah ne, wasu kuma na gumakansu ne, tare da cewa dukkansu na Allah ne, domin halittarsa ne kuma bayinsa ne.

3. Rashin hankalin mushirikai da rashin adalcinsu lokacin da suka jingina wa Allah abin da su suke ƙyama, watau 'ya'ya mata.
A nan ana warware muguwar aƙidar mushirikai ne ba ana nuna ƙasƙancin 'ya'ya mata ba ne.

4. Ɗabi'ar mata ta son ado da kwalliya, wanda su a wurinsu hakan kamala ce ba tawaya ba. Amma a wurin 'ya'ya maza ba shi ne kamala ba; kamala a wurinsu ita ce hankali da dogon tunani da fasahar zance.

5. Mushirikan Larabawa sun yi rashin adalci wajen dangana mala'iku zuwa ga Allah ta fuskoki uku:
Na farko, sun danganta wa Allah haihuwa.
Na biyu, sun ba shi mafi ƙasƙantar kaso sun ɗauki mafi daraja.
Na uku, sun ƙasƙanta mala'iku domin sun nuna 'ya'ya ne mata, ga shi kuwa su a aƙidarsu mata ƙasƙantattu ne.

Suratuz Zukhruf (15-19)
وَجَعَلُواْ لَهُۥ مِنۡ عِبَادِهِۦ جُزۡءًاۚ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَكَفُورٞ مُّبِينٌ ١٥ أَمِ ٱتَّخَذَ مِمَّا يَخۡلُقُ بَنَاتٖ وَأَصۡفَىٰكُم بِٱلۡبَنِينَ ١٦ وَإِذَا بُشِّرَ أَحَدُهُم بِمَا ضَرَبَ لِلرَّحۡمَٰنِ مَثَلٗا ظَلَّ وَجۡهُهُۥ مُسۡوَدّٗا وَهُوَ كَظِيمٌ ١٧ أَوَ مَن يُنَشَّؤُاْ فِي ٱلۡحِلۡيَةِ وَهُوَ فِي ٱلۡخِصَامِ غَيۡرُ مُبِينٖ ١٨ وَجَعَلُواْ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ ٱلَّذِينَ هُمۡ عِبَٰدُ ٱلرَّحۡمَٰنِ إِنَٰثًاۚ أَشَهِدُواْ خَلۡقَهُمۡۚ سَتُكۡتَبُ شَهَٰدَتُهُمۡ وَيُسۡـَٔلُونَ ١٩

15. Kuma suka mai da wasu daga cikin bayinsa wani ɓangare nasa (wato 'ya'yansa). Lalle mutum mai yawan butulci ne mai bayyana (butulcinsa)

16. Yanzu Ya ɗauki 'ya'ya mata daga abubuwan da Yake halitta, ku kuma Ya zaɓa muku 'ya'ya maza?

17. Idan kuma aka yi wa ɗayansu albishir da abin da ya buga misali cewa na (Allah) Arrahmanu ne, sai fuskarsa ta yini a murtuke yana cike da baƙin ciki.

18. Yanzu (sa danganta wa Allah) wanda da ake renon sa cikin kwalliya, alhali kuma idan an zo wajen husuma ba zai iya bayyana kansa (wajan ba da hujja) ba?

19. Suka kuma mai da malaʾiku waɗanda suke bayin (Allah) Arrahmanu ne ʻyaʻya mata. Shin sun halarci sanda aka halicce su ne? To za a rubuta shaidarsu, za kuma a tambaye su (a lahira).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana butulcin ɗanʾadam kafiri da rashin adalcinsa ga mahaliccinsa da cewa, mushirikai sun yi wa Allah ƙarya yayin da suka riya cewa wasu daga cikin halittunsa ʻyaʾyansa ne. Suna ɗaukar malaʾiku wai ʻyaʾyan Allah ne mata. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ya yi tir da wannan mummunan hali nasu, ya tabbatar da cewa lalle shi ɗanʾadam mai yawan butulci ne da nuna kafircinsa a fili.
Kuma Allah ya nuna irin rashin adalcin mushirikai a gare shi, domin su mata a wurinsu ƙasƙantattu ne, suna fifita maza a kansu, to amma kuma sai suka danganta masa mata da cewa su ne ʻyaʾyansa. Allah ya tambaye su game da wannan ɗanyen hukunci nasu da cewa, yanzu ya dace shi ya zaɓi ʻyaʾya mata daga cikin abin da ya halitta su kuma ya zaɓar musu maza? Hasali ma duk wanda aka kawo masa albishir daga cikinsu cewa an haifa masa ʻya mace, watau jinsin abin da yake ƙyama suke kuma jingina wa Allah, sai fuskarsa ta yini a murtuke yana cike da baƙin ciki, saboda tsananin takaici. To amma kuma ga shi yana jingina wa Allah mahalicci abin da shi yake tsananin ƙyama.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara nuna musu rashin dacewar abin da suka jingina masa na cewa malaʾiku ʻyaʾyansa ne mata da cewa, ita fa ʻya mace a ɗabiʾarta ta taso ne cikin son kwalliya da ado domin ta burge wasu, tana neman cike giɓin halittarta da wannan, shi ya sa ma tun tana jaririya ake huda kunnenta don yi mata ado da ɗan kunne, yayin da ɗa namiji ba ya buƙatar haka. Haka kuma idan an zo wajen husuma da jayayya mace ba za ta iya kawo wata hujjar da za ta kare kanta da ita ba, kamar yadda ɗa namiji zai yi. Ko kuma idan yaƙi ya ɓarke ba za ta iya taɓuka wani abu na ba da kariya ba.
Watau dai abin nufi a nan shi ne bayyana rashin tunanin mushirikai da rashin hankalinsu yayin da suka jingina wa Allah ɗa, suka kuma jingina masa ʻyaʻya mata raunana waɗanda su kansu suke ƙyamar su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo wata ƙwaƙƙwarar hujja da take ƙara tabbatar da ƙaryar masu jingina wa Allah ʻyaʾya kamar malaʾiku, da cewa malaʾiku fa dukkansu bayin Allah ne kuma halittarsa ne kamar yadda sauran halittunsa suke bayinsa. To amma sai su suka mayar da su mata kuma ʻyaʾyansa. To sai Allah ya tambaye su cewa, shin sun halarci lokacin halittarsu ne suka lura cewa su mata ne ba maza ba? To su sani cewa malaʾiku za su rubuta wannan shaidar tasu, kuma za a tambaye su game da ita a ranar alƙiyama, kuma za su ɗandani kuɗarsu a kanta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafa hujja da ƙaddara a kan yi wa Allah shirka, aikin mushirikai ne.

2. Bin hanyar wasu iyaye ko manya ko malamai ido-rufe ba tare da wani dalili ba, wannan ma ɓata ne.

3. Samun niʾima da wadata ga wanda bai san Allah ba, yana haifar masa da ɗagawa da girman kai da bijire wa masu yi masa nasiha.

4. Duk masu ƙaryata Allah da Manzonsa (ﷺ) ƙarshensu ba ya yin kyau.

Suratuz Zukhruf (20-25)

وَقَالُواْ لَوۡ شَآءَ ٱلرَّحۡمَٰنُ مَا عَبَدۡنَٰهُمۡۗ مَّا لَهُم بِذَٰلِكَ مِنۡ عِلۡمٍۖ إِنۡ هُمۡ إِلَّا يَخۡرُصُونَ٢٠ أَمۡ ءَاتَيۡنَٰهُمۡ كِتَٰبٗا مِّن قَبۡلِهِۦ فَهُم بِهِۦ مُسۡتَمۡسِكُونَ٢١
بَلۡ قَالُوٓاْ إِنَّا وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّهۡتَدُونَ٢٢ وَكَذَٰلِكَ مَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ فِي قَرۡيَةٖ مِّن نَّذِيرٍ إِلَّا قَالَ مُتۡرَفُوهَآ إِنَّا وَجَدۡنَآ
ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّقۡتَدُونَ٢٣ ۞قَٰلَ أَوَلَوۡ جِئۡتُكُم بِأَهۡدَىٰ مِمَّا وَجَدتُّمۡ عَلَيۡهِ ءَابَآءَكُمۡۖ قَالُوٓاْ إِنَّا بِمَآ أُرۡسِلۡتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ٢٤
فَٱنتَقَمۡنَا مِنۡهُمۡۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ٢٥

20. Suka kuma ce: "Da (Allah) Arrahmanu Ya ga dama, da ba mu bauta musu ba (wato mala'ikun)." Ba su da wani takamaiman ilimi a kan hakan; ba abin da suke yi sai shaci-fadi.

21. Ko kuma Mun ba su wani littafi ne gabaninsa (Alkur'ani), saboda haka suke rike da shi kam-kam?

22. A'a, cewa dai suka yi: "Lalle mu mun sami iyayenmu a kan wani addini ne, mu kuma lalle sawunsu muke bi."

23. Kuma kamar haka ne, ba Mu taba aiko wani mai gargadi ba a wata alkarya a gabaninka sai 'yan ta-moren cikinsu sun ce: "Lalle mu mun sami iyayenmu a kan wani addini, kuma lalle mu hanyarsu muke kwaikwayo."

24. Ya ce (da su: "Yanzu za ku yi koyi da su) ko da na zo muku da abin da ya fi zama shiriya a kan abin da kuka sami iyayenku a kansa?" Suka ce: "Lalle mu masu kafirce wa abin da aka aiko ku da shi ne."

25. Sai Muka saka musu da azaba; to duba ka ga yadda karshen masu karyatawa ya kasance.

A wadannan ayoyi Allah (Mai tsarki da daukaka) ya bayyana wani salo na izgilanci da kafirai suke yi yayin da ake yi musu wa'azi ana kiran su cewa, su daina bautar wasu ba Allah ba, sai kawai suka ka da baki suka ce, ai da Allah ya ga dama da ba zai kyale su suna bauta wa mala'ikun ba; tunda har aka ga ya kyale su suna bauta musu, to wannan ya nuna ya yarda da abin da suke yi. Sai Allah (Mai tsarki da daukaka) ya karyata su ya tabbatar da cewa ba su da wata hujja ta ilimi a kan wannan maganar tasu, suna dai kagen karairayi ne kawai suna danganta masa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da daukaka) ya tambaye su cewa, shin ya ba su wani littafi ne kafin Alkur'ani wanda a cikinsa ya halatta musu su bauta wa wasu ba Allah ba, don hake ne suke kankame masa?
Allah (Mai tsarki da daukaka) ya tabbatar da cewa sam ba su da wani littafi daga gare shi da ya ba su wannan damar; suna dai bin hanyoyin iyayensu ne kawai ido rufe ba tare da wata hujja ba, domin duk sanda aka fada musu gaskiya sai su bijire mata, su ce su sun sami iyayensu ne a kan wannan addinin da suke a kai na bautar gumaka, kuma su ba za su daina bin hanyoyinsu ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da daukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) da cewa, ba mutanensa ne kadai suka kafirce wa Allah da manzanninsa suka rika kafa hujja da iyayensu ba; babu wani manzo da ya aiko zuwa ga wata alkarya gabaninsa sai manyan cikin wannan alkarya sun fito suna kalubalantar sa suna tabbatar masa cewa su addinin da suke bi shi ne wanda suka gada iyaye da kakanni, kuma iyayen nasu za su ci gaba da bi sau da kafa ba ja da baya.
Sai manzon nasu ya tambaye su cikin mamaki cewa, yanzu za su bi hanyar iyayensu ko da kuwa abin da ya zo musu da shi ya fi zama shiriya a kan abin da suka samu iyayensu a kai? Sai kafiran suka tabbatar masa da cewa su fa sun kafirta da duk abin da aka saukar wa manzannin Allah ba ma shi kadai ba, watau ya daina bata wa kansa lokaci ba za su yi imani da shi ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ya saukar da azabarsa a kan al'ummun da suka ƙaryata manzanninsa, ya kuma umarci Manzonsa (ﷺ) ya duba ya ga yadda ƙarshen al'amarin masu ƙaryatawa ya kasance. Babu shakka ƙarshensu ya yi matuƙar muni. Don haka mutanensa ma ba su fi ƙarfin irin wannan azabar ta same su ba idan ba su yi imani ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin nesanta kai da duk wani kafirci da shirka.

2. Wanda ya ƙagi halitta daga babu shi ne ya cancanci a bautawa, kuma shi ne kaɗai mai nuna wa bawansa hanyar shiriya.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wanzar da kalmar Tauhidi a cikin zurriyyar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), domin iyaye sun riƙa yi wa 'ya'yansu wasiyya da ita, kamar yadda Annabi Ya'aƙubu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa 'ya'yansa irin wannan wasiyya.

Suratuz Zukhruf (26-28)

وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦٓ إِنَّنِى بَرَآءٌ مِّمَّا تَعْبُدُونَ ﴿٢٦﴾ إِلَّا ٱلَّذِى فَطَرَنِى فَإِنَّهُۥ سَيَهْدِينِ ﴿٢٧﴾ وَجَعَلَهَا كَلِمَةًۢ بَاقِيَةً فِى عَقِبِهِۦ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿٢٨﴾

26. Kuma ka tuna lokacin da Ibrahimu ya ce da Babansa da mutanensa: "Lalle ni ba ruwana da abin da kuke bautawa.

27. "Sai dai wanda Ya halicce ni, to lalle Shi ne Zai shirye ni."

28. Ya kuma sanya ta (kalmar Tauhidi ta zama) kalma ce mai wanzuwa a cikin zuri'arsa don (mutanen Makka) su komo (kan hanya)."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa mushirikan Larabawa labarin kakansu mai daraja Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda suke tutiyar cewa su suna bin addininsa ne, domin ya tabbatar musu cewa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai taɓa bautar wani ba Allah ba; hasali ma fitowa ya yi fili ya shaida wa babansa da mutanensa cewa, shi fa ba ruwansa da gumakan da suke bauta wa ba Allah ba. Shi abin bautarsa Ɗaya ne, shi ne Allah wanda ya ƙagi halittarsa, shi ne kuma zai nuna masa hanya miƙaƙƙiya ta bautarsa, watau yarda da cewa babu abin bauta wa da gaskiya sai shi kaɗai.
Sai Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya mayar da wannan kalma ta Tauhidi ta zama kalma mai wanzuwa a cikin zurriyarsa a bayansa, don haka sai aka yi ta samun masu kaɗaita Allah da bauta a cikinsu, ba sa haɗa shi da komai. Tabbas sanin wannan ga mushirikan Ƙuraishawa zai iya taimaka wa wasunsu su komo kan hanyar kakansu Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) su yi watsi da bautar gumaka su rungumi kalmar Tauhidi su bauta wa Allah shi kaɗai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jin dadîn rayuwar duniya da ƙyale-ƙyalenta yakan ja mutane zuwa ga bijire wa Allah da gaskiyar da ya aiko manzanninsa da ita.

2. Alƙur'ani da duk abin da ya ƙunsa na hukunce-hukunce da labarai gaskiya ne babu tababa a cikinsa.

3. Ma'aunin girma a wajen kafirai shi ne tarin dukiya da matsayi na duniya, wanda ba haka yake a wurin Allah ba.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai raba duk arziki tsakanin bayinsa, don haka shi ne ya fi cancanta ya zaɓi wanda zai ba wa annabci daga cikin bayinsa.

5. Da a ce kafiran Makka sun san haƙiƙanin mutane masu girma da daraja, da kuwa tabbas sun gane cewa a fadîn ƙasar Larabawa kakaf babu wani mai daraja da ɗaukaka da kyawawan halaye da zurfin tunani da yawan ilimi da hikima da yawan tausayi da rahama da ya kai kamar Annabi Muhammadu (ﷺ). Idan ana maganar kamala a cikin mutane shi ne ƙarshe, idan ana zancen ilimi da hikima da sanin yakamata shi ne maƙura. Duk duniya gaba ɗayanta babu kamarsa, masoyansa da maƙiyansa duk sun san haka. To ta yaya kafiran Makka za su fifita wani can a kansa, wanda bai kama ƙafarsa a martaba ko kamala ba; wanda maƙurar hankalinsa da tunaninsa shi ne ya ɗauki gumakan da ya sassaƙa daga itatuwa, ko ya gina da laka, yana bauta musu yana neman kusanci da su? Ina hankali ga mai irin wannan hali? Ina girma ga mai bautar abin da ba zai iya cutar da shi ko ya amfanar da shi ba?

6. Hikimar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wajen fifita bayinsa; wasu sukan fi wasu a wajen samun arziki na duniya, domin kowa ya ji yana da buƙata a wajen ɗan'uwansa, da haka ne rayuwar ɗan'adam za ta yiwu a bayan ƙasa.

7. Ni'imar addini ta fi ni'imar duniya a wurin Allah.

8. Duniya da abin da ta ƙunsa na ƙyale-ƙyalenta ba komai ba ne a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ya sa ya bai wa kafirai duk wani jin dadî na duniya, domin ya zama talala da fitina a gare su.

Suratuz Zukhruf (29-35)

بَلۡ مَتَّعۡتُ هَٰٓؤُلَآءِ وَءَابَآءَهُمۡ حَتَّىٰ جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ وَرَسُولٞ مُّبِينٞ ٢٩ وَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ قَالُواْ هَٰذَا سِحۡرٞ وَإِنَّا بِهِۦ كَٰفِرُونَ ٣٠ وَقَالُواْ لَوۡلَا نُزِّلَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ عَلَىٰ رَجُلٖ مِّنَ ٱلۡقَرۡيَتَيۡنِ عَظِيمٍ ٣١ أَهُمۡ يَقۡسِمُونَ رَحۡمَتَ رَبِّكَۚ نَحۡنُ قَسَمۡنَا بَيۡنَهُم مَّعِيشَتَهُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۚ وَرَفَعۡنَا بَعۡضَهُمۡ فَوۡقَ بَعۡضٖ دَرَجَٰتٖ لِّيَتَّخِذَ بَعۡضُهُم بَعۡضٗا سُخۡرِيّٗاۗ وَرَحۡمَتُ رَبِّكَ خَيۡرٞ مِّمَّا يَجۡمَعُونَ ٣٢ وَلَوۡلَآ أَن يَكُونَ ٱلنَّاسُ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ لَّجَعَلۡنَا لِمَن يَكۡفُرُ بِٱلرَّحۡمَٰنِ لِبُيُوتِهِمۡ سُقُفٗا مِّن فِضَّةٖ وَمَعَارِجَ عَلَيۡهَا يَظۡهَرُونَ ٣٣ وَلِبُيُوتِهِمۡ أَبۡوَٰبٗا وَسُرُرًا عَلَيۡهَا يَتَّكِـُٔونَ ٣٤ وَزُخۡرُفٗاۚ وَإِن كُلُّ ذَٰلِكَ لَمَّا مَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۚ وَٱلۡأٓخِرَةُ عِندَ رَبِّكَ لِلۡمُتَّقِينَ ٣٥

29. A'a, Na jiyar da waɗannan dadî tare da iyayensu ne har gaskiya ta zo musu da wani manzo mai bayyanawa.

30. Yayin da gaskiyar ta zo musu sai suka ce: "Wannan sihiri ne, kuma lalle mu masu kafirce masa ne."

31. Suka kuma ce: "Me ya hana a saukar da wannan Alƙur'ani ga wani babban mutum, daga alƙaryun nan guda biyu?"

32. Yanzu su ne suke raba rahamar Ubangijinka (ta annabci)? Mu ne Muka raba musu arzikinsu a rayuwar duniya. Muka kuma ɗaukaka darajojin sashinsu a kan sashi, don wani sashin ya riƙi wani sashi mai yi masa hidima. Rahamar Ubangijinka kuma ita ta fi abin da suke tarawa (na duniya).

33. Ba don kuma kada mutane su zama iri ɗaya ba, da sai Mu sanya wa waɗanda suke kafirce wa (Allah) Mai rahma rufi na azurfa a gidajensu, da kuma matattakala (irinta), da za su riƙa hawa ta kansu.

34. Kuma (Mu sanya wa) gidajen nasu ƙofofi da gadaje da za su riƙa kishingiɗa a kansu.

35. Kuma (Mu sanya musu) zinariya. Duk waɗannan ba komai ba ne sai ɗan jin daɗin rayuwar duniya. Lahira kuma a wurin Ubangijinka ta masu taƙawa ce.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa bai gaggauto wa mushirikai azaba ba; ya ƙyale su ne, ya kuma jiyar da su daɗi, sun yi tsawon rai, sun sami ni'ima ta duniya; su ma iyayensu ya jiyar da su daɗi suka yi ta bin sha'awe-sha'awensu har lokacin da Alƙur'ani ya zo musu da Manzo mai bayyana gaskiya, watau Annabi Muhammadu (ﷺ).
To lokacin da Alƙur'ani ya zo musu sai suka ƙaryata shi suka ce sihiri ne, kuma suka yi iƙirari da cewa su sun kafirce masa ba za su yi imani da shi ba.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani shisshigi na mushirikai da rashin ladabinsu gare shi, yayin da suka fito fili suka ce wai me ya sa lokacin da Allah ya tashi saukar da Alƙur'ani bai saukar da shi ga wani babban mutum daga alƙaryun nan guda biyu ba? Watau suna nufin me ya sa bai saukar da shi ga Al-Walid ɗan Mughira a Makka ko kuma Urwatu ɗan Mas'ud a Ɗa'ifa ba, maimakon haka sai ya saukar wa Muhammadu ɗan Abdullahi wanda yake shi talaka ne ba shi da komai?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su cewa, shin wai su ne suke raba rahamar Ubangiji, su ba wa wanda suka ga dama, su hana wanda suka ga dama, ko kuma Allah ne yake rabawa? Don haka shi ya ga dama ya zaɓi Annabi Muhammadu (ﷺ) ya ba shi annabta. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi ne mai raba komai, domin shi ne ya raba musu arzikinsu a duniya, ya yi wani mawadaci wani kuma matalauci, ya ɗaukaka wani a kan wani wajen samu da matsayi na duniya, don wasu su zama masu yin hidima ga wasu. Kuma lalle su sani cewa, rahamar Allah ga bayinsa a lahira ta fi abin da suke tarawa na tarkacen duniya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu ƙaskancin duniya da wulaƙantarta a wurinsa, inda ya bayyana cewa, ba don kada mutane gaba ɗayansu su zama kafirai ba, da sai ya sanya wa gidajen waɗanda suka kafirce masa rufi na azurfa, ya sanya musu matattakala ita ma ta azurfa, wadda za su riƙa takawa suna hawa ta kanta. Ya kuma sanya wa gidajensu ƙofofi da gadaje na alfarma da za su riƙa kishingiɗa a kansu, ya kuma ba su kayan ado na zinare, don hakan ya zama talala a gare su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa duk wannan ƙyale-ƙyale da kayan more rayuwa ba komai ba ne a wurinsa sai wani ɗan jin daɗin rayuwar duniya wanda bai taka kara ya karya ba, idan aka kwatanta shi da na lahira wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanade shi musamman saboda bayinsa masu taƙawa, watau masu aiki da umarnisa da guje wa haninsa.

An karɓo daga Sahlu ɗan Sa'ad (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Da a ce duniya ta kai darajar fiffiken sauro a wurin Allah, to da bai shayar da kafiri maƙwarwa ɗaya ta ruwa daga gare ta ba." [Tirmizi #2320, dubi Al-Albani, *As-Sahiha* #686].

Daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) , daga Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Lokacin da na shiga wurin Manzon Allah (ﷺ) sai na same shi kishingiɗe a kan tabarma babu wata shimfiɗa a kanta, har kabar tabarmar ta yi masa alama a ɓarin jikinsa, yana kishingiɗe a kan wani matashin kai na jemammiyar fata wanda aka cika shi da zaren itaciyar dabino. Na kuma ɗaga kaina na dubi ko'ina a cikin wannan gidan nasa, na rantse da Allah ban ga wani abu mai jan hankali ba sai wasu buzaye guda uku. Sai na ce: 'Ka roƙi Allah ya yalwata arzikin al'ummarka, domin ya yalwata wa mutanen Farisa da Rum, ya ba su duniya ga shi ba sa ma bautar Allah'. Annabi (ﷺ) yana kishingiɗe, da jin haka sai ya tashi zaune ya ce: "Shin kana cikin kokwanto ne ya kai Ɗan Khaɗɗab? Waɗancan da kake magana, mutane ne da Allah ya

gaggauto musu da jin daɗinsu a nan duniya.'' Sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: ''Ya Manzon Allah, ka nema mini gafarar Allah.'' [Bukhari #2468 da Muslim #1479].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur'ani shi ne mafi girman rahamar Allah ga bayinsa, duk wanda ya rungume shi ya yi imani da karantarwarsa to ya dace da mafi girman kyauta, ya kuma rabauta duniya da lahira. Wanda kuwa ya bijire masa, to ya taɓe ya yi hasarar da ba zai taɓa rabauta bayanta ba har abada.

2. Duk wanda ya saki Alƙur'ani, to lalle ya ƙulla abota da Shaiɗan abota ta har abada, ba zai taɓa ƙyale shi ya aikata wani alheri a rayuwarsa ba.

3. Duk wanda zai ƙulla abota da mutumin da zai raba shi da hanyar Allah, to zai zo ranar alƙiyama yana nadamar ƙulluwar wannan abotar a tsakaninsu, a lokacin da nadama ba za ta amfane shi da komai ba.

4. Idan a duniya haɗuwar mutane cikin wata masifa tana sanya musu jin sanyin raɗaɗinta, domin mutum yakan ga ba shi kaɗai ne masifar ta shafa ba, suna da yawa waɗanda abin ya shafa. To irin wannan a lahira ba zai amfani kafirai ba, yayin da aka jefa su cikin wuta; kowa zai riƙa ji ne kamar azabarsa ta fi ta ɗan'uwansa, don haka ba zai ji sassauci a ransa ba.

Suratuz Zukhruf (36-39)
وَمَن يَعۡشُ عَن ذِكۡرِ ٱلرَّحۡمَٰنِ نُقَيِّضۡ لَهُۥ شَيۡطَٰنٗا فَهُوَ لَهُۥ قَرِينٞ ٣٦ وَإِنَّهُمۡ لَيَصُدُّونَهُمۡ عَنِ ٱلسَّبِيلِ وَيَحۡسَبُونَ أَنَّهُم مُّهۡتَدُونَ ٣٧ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَنَا قَالَ يَٰلَيۡتَ بَيۡنِي وَبَيۡنَكَ بُعۡدَ ٱلۡمَشۡرِقَيۡنِ فَبِئۡسَ ٱلۡقَرِينُ ٣٨ وَلَن يَنفَعَكُمُ ٱلۡيَوۡمَ إِذ ظَّلَمۡتُمۡ أَنَّكُمۡ فِي ٱلۡعَذَابِ مُشۡتَرِكُونَ ٣٩

36. Wanda kuwa ya zama mai dundumi game da ambaton (Allah) Mai rahma, to za Mu haɗa shi da Shaiɗan ya zama shi ne abokinsa.

37. Lalle kuma su (shaiɗanun) tabbas suna kange su daga tafarki nagari, su kuma suna zato cewa lalle su shiryayyu ne.

38. Har zuwa lokacin da suka zo mana (wato mutumin da shaiɗaninsa) sai ya ce: ''Ina ma a ce tsakanina da kai akwai nisan gabas da yamma; to tir da aboki irinka.''

39. (Allah Ya ce da su): ''A yau tun da kun riga kun yi zalunci zamantowarku tare a cikin azaba ba zai amfane ku ba

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin uƙubarsa ga wanda ya makance da gangan ya bijire wa Alƙur'ani wanda shi ne mafi girman rahamar Allah ga bayinsa, da cewa duk wanda ya aikata haka to kansa ya cuta, domin kuwa ya jawo Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa shi da wani shaiɗani da zai ƙulla abota da shi ba dare ba rana, ya yi ta ƙara ingiza shi cikin ɓata da hallaka.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, waɗannan shaiɗanun abokan masu bijire wa Alƙur'ani za su yi ta hana su bin tafarkin Allah, sai su ƙi bin umarninsa su ƙi guje wa haninsa, duk da haka kuma su riƙa zaton su shiryayyu ne suna kan gaskiya, don haka ba su da ranar tuba su koma ga Allah. Har sai lokacin da ɗayansu ya gamu da Allah ranar alƙiyama, a lokacin ne zai cika da nadama marar amfani, ya riƙa burin ina ma a ce tsakaninsa da abokinsa shaiɗani akwai tazara mai nisan gabas da yamma a tsakaninsu. Sai ya yi tir da wannan aboki nasa, ya nesanta kansa da shi.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa mushirikai waɗanda suka zalunci kansu da kafirci cewa, haɗuwarsu tare a cikin azabar wutar Jahannama ba za ta amfane su da komai ba a wannan ranar, domin babu wani daga cikinsu da zai iya rage wa wani tsananin azabar da yake ciki. Kuma kasancewarsu duk sun haɗu a cikin wuta wannan ba zai sa su ji sanyi-sanyi a zukatansu ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) an yi masa umarnin da ya yi riƙo da wahayin da Allah ya yi masa ya yi aiki da koyarwarsa.

2. Alƙur'ani ɗaukaka ne ga Manzon Allah (ﷺ) da al'ummarsa. Kuma ɗaukaka ne ga Larabawa, domin a cikin harshensu Allah ya saukar da shi, don haka su za su fi kowa fahimtar sa, saboda haka ya kamata su fi kowa bin sa sau da ƙafa, su fi kowa aiki da karantarwasa. Haka kuwa zaɓaɓɓun cikinsu suka kasance kamar Al-Muhajiruna waɗanda suka riga kowa shiga Musulunci da waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa.

3. Dukkanin manzannin Allah sun haɗu akan watsi da shirka da bautar wanin Allah.

Suratuz Zukhruf (40-45)
أَفَأَنتَ تُسۡمِعُ ٱلصُّمَّ أَوۡ تَهۡدِي ٱلۡعُمۡيَ وَمَن كَانَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٤٠ فَإِمَّا نَذۡهَبَنَّ بِكَ فَإِنَّا مِنۡهُم مُّنتَقِمُونَ ٤١ أَوۡ نُرِيَنَّكَ ٱلَّذِي وَعَدۡنَٰهُمۡ فَإِنَّا
عَلَيۡهِم مُّقۡتَدِرُونَ ٤٢ فَٱسۡتَمۡسِكۡ بِٱلَّذِيٓ أُوحِيَ إِلَيۡكَۖ إِنَّكَ عَلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٤٣ وَإِنَّهُۥ لَذِكۡرٞ لَّكَ وَلِقَوۡمِكَۖ وَسَوۡفَ تُسۡـَٔلُونَ ٤٤ وَسۡـَٔلۡ مَنۡ
أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رُّسُلِنَآ أَجَعَلۡنَا مِن دُونِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ءَالِهَةٗ يُعۡبَدُونَ ٤٥

40. Yanzu kai ka iya jiyar da kurme, ko kuma ka iya shiryar da makafi da wanda ya kasance cikin ɓata mabayyani?

41. To idan Muka karɓi ranka, to lalle Mu Masu yi musu uƙuba ne.

42. Ko kuma Muka nuna maka irin abin da muka yi musu alƙawarin narko da shi, to lalle Mu Masu iko ne a kansu.

43. To ka riƙe abin da aka yi maka wahayinsa; lalle kai kana kan hanya madaidaiciya.

44. Kuma lalle shi (Alƙur'ani) ɗaukaka ce a gare ka da mutanenka; ba da daɗewa ba kuma za a tambaye ku (game da haƙƙinsa).

45. Ka tambayi waɗanda Muka aiko gabaninka daga manzanninmu, shin Mun sanya wasu ababen bauta da ake bauta musu ba (Allah) Mai rahma ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rarrashi Manzonsa (ﷺ) ne game da damuwar da yake ciki dangane da kafircin mutanensa da yadda suke ta ƙara taurin kai da bijire wa kiransa da cewa, ya sani fa ba zai iya jiyar da kurame ba, ko kuma ya shiryar da makafi ko ya shiryar da wanda ya yi nisa cikin ɓata mabayyani ba. Watau kamar dai yadda kurma ba zai taɓa jin wata murya ba, makaho kuma ba zai iya ganin komai ba, ko kuma wanda ya ɓace ɓat ba zai taɓa gane hanya ba, to hakanan su ma waɗannan mutanen nasa zukatansu sun riga sun lalace, hankulansu sun gurɓata saboda sun bijire wa sauraron Alƙur'ani da wa'azi, don haka sun sanya katangar ƙarfe tsakaninsu da shiriyar Allah.

Waɗannan mutane ba abin da ya rage musu sai azabar Allah ta zo musu, ko dai tun a nan duniya ko kuma in sun je lahira. To saboda haka Allah ya kwantar wa da Manzonsa (ﷺ) hankali da cewa, ko da ya karɓi ransa kafin yi musu azaba, to lalle zai azabtar da su a duniya da lahira. Idan kuma Allah ya ga dama sai ya nuna masa wani yanki na azabar da yake yi musu alƙawarinta, domin Allah mai iko ne a kan komai babu abin da ya fi ƙarfinsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya ƙanƙame abin da ya yi masa wahayinsa ya yi aiki da shi, ya tabbatar masa cewa lalle shi yana bisa hanya madaidaiciya wadda babu ruɗani a cikinta.
Ya kuma tabbatar masa, har ila yau, cewa Alƙur'ani ɗaukaka ce a gare shi, shi da mutanensa, domin ɗimbin alherin da ya ƙunsa, don haka su sani cewa sai an tambaye su a lahira game da wannan Alƙur'ani; shin sun yi imani da shi sun bi karantarwarsa sun kira mutane zuwa gare shi ko kuwa a'a?
Sai kuma ya umarci Annabi (ﷺ) ya tambayi manzannin da ya aiko gabaninsa ya ji cewa, shin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya wasu alloli ana bauta musu ba shi ba? Watau da Manzo (ﷺ) zai bibiyi labaransu ya yi tambaya a kansu, ba zai sami manzo ɗaya ba da ya yi kira a bauta wa wani tare da Allah. Wannan ya tabbatar da cewa mushirikai ba su da wata hujja ta wahayi ko ta hankali a kan abin da suke yi na bautar wanin Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Izgili da yi wa muminai dariya mummunar ɗabi'a ce ta kafirai.

2. Warware alƙawari siffa ce ta kafirai.

3. Duk wani fasiƙi mutum ne mai raunin hankali, don haka da wuri ake raina masa hankali a ruɗe shi har ya hallaka kansa a banza.

4. Nuni zuwa ga cewa mushirikan Makka masu ganin Annabi Muhammadu (ﷺ) ba babban mutum ne wanda ya cancanci annabta ba, sun maimaita irin abin da Fir'auna ya nuna wa Annabi Musa ne na ganin bai cancanci a gaskata shi ba, domin wai shi talaka ne ba shi da komai. Kuma wai shi Fir'auna shi ne mai gaskiya saboda mulkin Misra nasa ne, kuma ga duniya an ba shi.

5. Fushin Allah ga mutane yana jawo musu azabarsa da hasara duniya da lahira.

Suratuz Zukhruf (46-56)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَإِۡيهِۦ فَقَالَ إِنِّي رَسُولُ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ۝٤٦ فَلَمَّا جَآءَهُم بِـَٔايَٰتِنَآ إِذَا هُم مِّنۡهَا يَضۡحَكُونَ ۝٤٧ وَمَا نُرِيهِم مِّنۡ ءَايَةٍ إِلَّا هِيَ أَكۡبَرُ مِنۡ أُخۡتِهَاۖ وَأَخَذۡنَٰهُم بِٱلۡعَذَابِ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ۝٤٨ وَقَالُواْ يَٰٓأَيُّهَ ٱلسَّاحِرُ ٱدۡعُ لَنَا رَبَّكَ بِمَا عَهِدَ عِندَكَ إِنَّنَا لَمُهۡتَدُونَ ۝٤٩ فَلَمَّا كَشَفۡنَا عَنۡهُمُ ٱلۡعَذَابَ إِذَا هُمۡ يَنكُثُونَ ۝٥٠ وَنَادَىٰ فِرۡعَوۡنُ فِي قَوۡمِهِۦ قَالَ يَٰقَوۡمِ أَلَيۡسَ لِي مُلۡكُ مِصۡرَ وَهَٰذِهِ ٱلۡأَنۡهَٰرُ تَجۡرِي مِن تَحۡتِيٓۚ أَفَلَا تُبۡصِرُونَ ۝٥١ أَمۡ أَنَا۠ خَيۡرٞ مِّنۡ هَٰذَا ٱلَّذِي هُوَ مَهِينٞ وَلَا يَكَادُ يُبِينُ ۝٥٢ فَلَوۡلَآ أُلۡقِيَ عَلَيۡهِ أَسۡوِرَةٞ مِّن ذَهَبٍ أَوۡ جَآءَ مَعَهُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ مُقۡتَرِنِينَ ۝٥٣ فَٱسۡتَخَفَّ قَوۡمَهُۥ فَأَطَاعُوهُۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمٗا فَٰسِقِينَ ۝٥٤ فَلَمَّآ ءَاسَفُونَا ٱنتَقَمۡنَا مِنۡهُمۡ فَأَغۡرَقۡنَٰهُمۡ أَجۡمَعِينَ ۝٥٥ فَجَعَلۡنَٰهُمۡ سَلَفٗا وَمَثَلٗا لِّلۡأٓخِرِينَ ۝٥٦

46. Haƙiƙa kuma Mun aiko Musa da ayoyinmu zuwa ga Fir'auna da manyan fadawansa, sai ya ce: ''Lalle ni Manzo ne na Ubangijin talikai.''

47. To lokacin da ya zo musu da ayoyinmu sai ga su suna yi musu dariya.

48. Ba Mu kuma nuna musu wata aya ba sai wadda take ta fi ‘yar’uwarta girma; Muka kuma kama su da azaba don su dawo (kan hanya).

49. Suka kuma ce: “Ya kai wannan mai sihiri, ka roƙa mana Ubangijinka da abin da Ya yi maka wahayinsa (Ya yaye mana azaba), lalle mu tabbas za mu shiriya.”

50. To lokacin da Muka yaye musu azabar sai ga su suna warware alƙawari.

51. Fir’auna kuma ya yi shela a cikin mutanensa ya ce: “Ya ku mutanena, yanzu mulkin Misra ba nawa ba ne, kuma ga ƙoramu suna ta kwarara ta ƙarƙashina, ko ba kwa gani ne?

52. “A’a, ni na fi wannan wulaƙantaccen wanda da ƙyar yake iya bayani.

53. “To me ya hana a saukar masa da warawarai na zinare, ko kuma wasu mala’iku su zo tare da shi suna masu dafa masa baya?”

54. Sai ya yi wasa da hankalin mutanensa sai suka bi shi. Lalle su sun kasance mutane ne fasiƙai.

55. To lokacin da suka fusata Mu sai Muka saukar musu da uƙuba, Muka nutsar da su ga baki ɗaya.

56. Sai Muka sanya su ja-gaba (wajen hallakarwa), kuma wa’azi ga na baya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba da labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne yayin da ya aike shi zuwa ga Fir’auna da manyan fadawansa, ya ba shi mu’ujizoji masu tabbatar da gaskiyarsa, kamar sandarsa mai rikiɗewa ta zama macijiya da hannunsa mai haske kamar fitila.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yayin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya je musu ya shaida musu cewa lalle shi Manzo ne daga Allah Ubangijin dukkan halittu, to amma maimakon Fir’auna da fadawansa su yi imani da shi sai kawai suka ɓige da yi masa dariya suna yi masa izgili.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da nuna wa Fir’auna da mutanensa hujjoji masu tabbatar da manzancin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Duk sanda ya tashi nuna musu wata hujja to yakan nuna musu hujjar da ta fi wadda ta gabace ta girma, domin Fir’auna da mutanensa su gamsu, to amma sai suka ci gaba da bijirewa da kafircewa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kama su da azabar duniya don su dawo kan hanya, kamar azabar fari da kwaɗi da jini da sauransu, to amma kuma wannan bai amfana musu komai ba.
A duk lokacin da wata azaba ta auka musu sai su roƙi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya roƙa musu Ubangijinsa saboda wahayin da ya yi masa na cewa idan sun yi imani zai yaye musu azaba. Sai su tabbatar masa da cewa za su yi imani idan har ya yaye musu ita, za su shiriya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da zarar ya yaye musu azabar sai su warware alƙawarin da suka yi masa, su ci gaba da kafircinsu.
Shi kuma Fir’auna, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da mu cewa, ya ci gaba da yi wa mutanensa burga yana tinƙaho da ƙarfin mulkinsa, yana nuna musu cewa shi ne mai sarauta a Misra gaba ɗayanta, sannan ga shi ya gina tafka-tafkan gidaje na alfarma waɗanda ya ja ƙoramu suna gudana ta ƙarƙashinsu. Don haka su duba su ga irin wannan matsayi nasa da ƙarfin mulki da arziki da yake da shi. Saboda haka ya

nuna musu cewa yanzu shi ya kamata su bi, ko kuma za su bi Musa wanda yake wulaƙantacce talaka marar gata wanda ko magana bai iya ba?
Sannan Fir'auna ya nuna wa mutanensa cewa idan Musa da gaske Allah ne ya aiko shi me ya hana ya haɗo shi da kayan ado na warawarai na zinare ko wasu mala'iku su zo tare da shi suna gaskata shi?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa Fir'auna ya raina hankalin mutanensa har ya ruɗe su da maganganunsa na shirme, su kuma suka bi shi a kan ɓatansa, domin su mutane ne fasiƙai, shi ya sa Fir'auna ya sami lagonsu har ya ƙara dulmiyar da su cikin ɓata da hallaka.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yayin da Fir'auna da mutanensa suka fusata shi suka dage a kan kafircinsu da ƙaryata Annabi Musa, sai ya saukar musu da azabarsa, ya nutsar da su cikin kogi dukkansu suka hallaka, ya kuma tserar da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka yi imani da shi daga Banu Isra'ila.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya Fir'auna da manyan fadawansa suka zamanto ja-gaba wajen hallakarwa, kafiran Makka kuma suna tafe a bayansu. Ya mayar da su wa'azi ga wanda zai wa'azantu ya guji irin aikinsu don kada irin abin da ya same su shi ma ya same shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin jayayyar kafirai ba a kan ƙarya.

2. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bawan Allah ne wanda ya ba wa annabta, ba abin bauta ba ne.

3. Cikin hikimomin samar da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba uba akwai nuna wa Banu Isra'ila cikar Ƙudurar Allah da jaddada musu imaninsu bayan dogon lokaci da aka ɗauka ba a aiko musu da wani manzo ba.

4. Tabbatar wa da Larabawa masu bautar mala'iku cewa, su ma mala'iku bayin Allah ne, shi ne ya ga dama ya sanya mazauninsu a sama, da ya so da ya sanya su a ƙasa maimaikon mutane, ya zartar musu irin abin da ya zartar a kan mutane na aiko musu manzanni da kallafa musu bauta.

Suratuz Zukhruf (57-60)
*وَلَمَّا ضُرِبَ ٱبۡنُ مَرۡيَمَ مَثَلًا إِذَا قَوۡمُكَ مِنۡهُ يَصِدُّونَ ٥٧ وَقَالُوٓاْ ءَأَٰلِهَتُنَا خَيۡرٌ أَمۡ هُوَۚ مَا ضَرَبُوهُ لَكَ إِلَّا جَدَلَۢاۚ بَلۡ هُمۡ قَوۡمٌ خَصِمُونَ ٥٨ إِنۡ هُوَ إِلَّا عَبۡدٌ أَنۡعَمۡنَا عَلَيۡهِ وَجَعَلۡنَٰهُ مَثَلٗا لِّبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٥٩ وَلَوۡ نَشَآءُ لَجَعَلۡنَا مِنكُم مَّلَٰٓئِكَةٗ فِي ٱلۡأَرۡضِ يَخۡلُفُونَ ٦٠

57. Lokacin da kuwa aka buga misali da (Isa) ɗan Maryamu, sai ga mutanenka suna ta annashawa game da shi.

58. Suka kuma ce: "Yanzu ababen bautar mu ne suka fi ko kuwa shi (Isa)?" Ba su buga maka misali da shi ba sai don son jayayya. Ba shakka su dai mutane ne masu tsananin jayayya.

59. Shi (Isa) ba wani ba ne face bawa ne da Muka yi masa ni'ima, Muka kuma sanya shi abin buga misali ga Bani-Isra'ila.

60. Da kuma za Mu ga dama tabbas da Mun sanya mala'iku ne za su maye gurbinku a bayan ƙasa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafiran Makka suka riƙa jayayya da Manzon Allah (ﷺ) don tabbatar da bautar gumakansu, lakacin da suka ji Manzon Allah (ﷺ) yana hana su bautar wani ba Allah ba, yana nuna musu cewa, su da duk abubuwan da suke bauta wa ba Allah ba gaba ɗayansu wuta za su.

Ibn Is'haƙ ya ruwaito a cikin littafinsa na Sira cewa, wata rana Manzon Allah (ﷺ) yana zaune a Masallacin Makka tare da wasu manyan Ƙuraishawa irin su Al-Walid ɗan Mugira da Nadhru ɗan Haris, sai suka shiga jayayya da shi a kan bautarsu ta gumaka, sai Manzon Allah (ﷺ) ya karanta musu faɗar Allah: "Lalle ku da abin da kuke bauta wa ba Allah ba, (duka) makamashin Jahannama ne, kuma ku masu shigar ta ne." [*Al-Anbiya* aya ta 98].
Sai Abdullahi ɗan Az-Ziba'ara ya shigo ya zauna, da aka gaya masa abin da Annabi (ﷺ) yake karantawa sai ya ce: "Wallahi sai na ƙure shi da hujja, ku tambayi Muhammadu, shin duk abin da aka bauta wa ba Allah ba za a sa shi wutar Jahannama tare da wanda ya bauta masa kenan? To mu muna bautar mala'iku, Yahudawa kuma suna bauta wa Uzairu, Nasara kuma suna bauta wa Isa ɗan Maryam, watau duk za su tafi wuta kenan?"
Da jin haka sai mushirikai suka yi ta murna suna shewa wai an ƙure Manzon Allah (ﷺ) da hujja. Yayin da Manzon Allah (ﷺ) ya ji abin da Ɗan Az-Ziba'ara ya faɗa sai ya ce: "Lalle duk wanda ya so a bauta masa ba Allah ba, to yana tare da wanda ya bauta masa, kuma lalle su shaiɗanu suke bauta wa da wanda suka umarta a bauta masa." Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "Lalle waɗanda kalmarmu mafi kyau (ta cewa, su 'yan Aljanna ne) ta riga ta tabbata a gare su, waɗannan waɗanda ake nesantawa ne daga gare ta (wutar). Ba za su ji hargowarta ba, kuma su masu dawwama ne a cikin abin da ransu yake so." [Al-Anbiya, aya ta 100-101].
Watau mala'iku da Uzairu da Annabi Isa da sauran mutane nagari da aka bauta wa ba da yardarsu ba, ba za a sa su a wuta ba. [Dubi, Ibn Hisham, *As-Sira*, Juzu'i na 1, shafi na 359-360].

A nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana bayyana cewa lokacin da Ibnu Az-Ziba'ara ya ba da misali da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don ya ƙure Manzon Allah (ﷺ) mushirikan Makka sun yi ta sowa suna murna, suna cewa "Mun yarda allolinmu su zama kamar Isa, watau idan har za a sa Isa tare da masu bautarsa wuta, to mu ma za a sa mu tare da gumakanmu, domin ababen bautarmu ne suka fi ko Isa?" Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, wannan misalin da suka ba shi na Annabi Isa ba niyyarsu fahimtar gaskiya ba ne, manufarsu kawai ita ce jayayya don tabbatar da ƙarya, domin su da man mutane ne masu tsananin jayayya da husuma.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa shi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba wani ne ba face bawa daga cikin bayin Allah da ya ni'imta shi da annabta da manzanci, ya kuma sa shi misali ga Banu Isra'ila don su gane cikar Ƙudurar Allah yayin da ya halicce shi ba uba kamar yadda ya halicci Annabi Adamu ba uwa ba uba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tsoratar da su da cewa da ya ga dama da sai ya hallaka su, ya kawo mala'iku a maimakonsu su maye gurbin 'yan'adam a bayan ƙasa, su yi ta bautar Allah ba tare da suna haɗa shi da komai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dawowar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) alama ce daga cikin manyan alamomin tashin alƙiyama.

2. Shakka game da zuwan alƙiyama kafirci ne.

3. Tsananin adawar Shaiɗan ga 'yan'adam.

4. Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo ne domin ya cike shari'ar Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da hukunce-hukuncen Attaura, ya halatta wa Banu Isra'ila wani sashin abin da aka haramta musu.

5. Tabbatar da Tauhidur Rububiyya, watau imani da cewa Allah ne kaɗai mai halitta mai ni'imta abin da ya halitta da dangogin ni'imominsa na sarari da na ɓoye. Akwai kuma tabbatar da Tauhidul Uluhiyya, watau kaɗaita Allah da bauta da guje wa shirka.

6. Tabbatar da cewa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bawan Allah ne, ba kamar yadda Nasara suke da'awar cewa shi ɗan Allah ne ba, ko ɗayan alloli uku.

7. Karkasuwar Nasara ƙungiya-ƙungiya game da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan ɗauke shi zuwa sama ta biyu.

Suratuz Zukhruf (61-65)

وَإِنَّهُۥ لَعِلۡمٞ لِّلسَّاعَةِ فَلَا تَمۡتَرُنَّ بِهَا وَٱتَّبِعُونِۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٦١ وَلَا يَصُدَّنَّكُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُۖ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ٦٢ وَلَمَّا جَآءَ عِيسَىٰ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ قَالَ قَدۡ جِئۡتُكُم بِٱلۡحِكۡمَةِ وَلِأُبَيِّنَ لَكُم بَعۡضَ ٱلَّذِي تَخۡتَلِفُونَ فِيهِۖ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ٦٣ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ رَبِّي وَرَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُوهُۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٦٤ فَٱخۡتَلَفَ ٱلۡأَحۡزَابُ مِنۢ بَيۡنِهِمۡۖ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنۡ عَذَابِ يَوۡمٍ أَلِيمٖ ٦٥

61. Lalle kuma shi (Isa) alama ce ta zuwan alƙiyama, kada ku yi shakka game da ita, kuma ku bi Ni. Wannan ita ce hanya madaidaiciya.

62. Kada kuma Shaiɗan ya kange ku; lalle shi maƙiyi ne mai bayyana (ƙiyyaya) a gare ku.

63. Lokacin da kuma Isa ya zo da hujjoji bayyanannu ya ce: "Haƙiƙa na zo muku da hikima, don kuma in bayyana muku sashin da kuke sassaɓawa cikinsa; to ku kiyaye dokokin Allah, kuma ku bi ni.

64. "Lalle Allah Shi ne Ubangijina kuma Ubangijinku, sai ku bauta masa. Wannan ita ce hanya madaidaiciya."

65. Sai ƙungiyoyi suka sassaɓa a tsakaninsu; don haka tsananin azabar yini mai raɗaɗi ya tabbata ga waɗanda suka yi zalunci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin matsayin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) inda ya nuna cewa shi alama ce daga cikin alamomin tashin alƙiyama, lokacin da zai sauko daga sama ta biyu a ƙarshen zamani. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana mutane su rika shakka game da zuwan ranar alƙiyama domin sai ta tabbata babu makawa. Ya kuma umarce su da su bi shi game da duk abin da yake labarta musu su gaskata shi, domin wannan shi ne hanya madaidaiciya.
Sai kuma Allah ya tsawatar musu da cewa, kada su bari Shaiɗan ya hana su bin hanyar Allah miƙaƙƙiya da rudìnsa da yaudararsa, domin shi maƙiyinsu ne mai bayyana ƙiyayya a gare su.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa yayin da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya je wa mutanensa da dalilai bayyanannu a kan cewa shi lalle Manzon Allah ne, ya shaida musu cewa ya zo musu da wata hikima daga Allah, watau annabci da wahayi, kuma don ya yi musu bayanin wani ɓangare na addininsu da suke saɓani a kansa. Ya ja hankalinsu a kan su kiyaye dokokin Allah su bi umarninsa su guje wa haninsa, shi ma su yi masa biyayya cikin umarninsa da haninsa. Ya tabbatar musu cewa Allah ne

Ubangijinsa su ma shi ne Ubangijinsu, ba su da wani abin bauta ba shi ba, don haka su tsarkake shi da bauta shi kaɗai. Wannan Tauhidin shi ne miƙaƙƙiyar hanya da babu karkata tare da ita.
To amma duk da wannan bayani da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi musu sai ga shi wasu ƙungiyoyi a tsakaninsu sun sassaɓa dangane da shaʾaninsa; wasu suka ce shi Allah ne, wasu kuma suka ce ɗan Allah ne, wasu kuma suka ce shi da mahaifiyarsa duka alloli ne. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa duk waɗanda suka yi zalunci wajen allantar da Annabi Isa da mahaifiyarsa ko daʾawar cewa ɗan Allah ne, to tsananin azaba ya tabbata a gare su a ranar alƙiyama wadda tana nan tana jiran su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wata abota da soyayya ba za su yi amfani ba a lahira sai soyayyar da aka yi don Allah.

2. Albishir ga muminai da kwantar musu da hankali game da abin da za su fuskanta a nan gaba ko wanda suka bari a baya.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gadar wa muminai gidan Aljanna saboda kyawawan ayyukansu da falalarsa.

Suratuz Zukhruf (66-73)
هَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّا ٱلسَّاعَةَ أَن تَأۡتِيَهُم بَغۡتَةٗ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ٦٦ ٱلۡأَخِلَّآءُ يَوۡمَئِذِۢ بَعۡضُهُمۡ لِبَعۡضٍ عَدُوٌّ إِلَّا ٱلۡمُتَّقِينَ٦٧ يَٰعِبَادِ لَا خَوۡفٌ عَلَيۡكُمُ ٱلۡيَوۡمَ وَلَآ أَنتُمۡ تَحۡزَنُونَ٦٨ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَكَانُواْ مُسۡلِمِينَ٦٩ ٱدۡخُلُواْ ٱلۡجَنَّةَ أَنتُمۡ وَأَزۡوَٰجُكُمۡ تُحۡبَرُونَ٧٠ يُطَافُ عَلَيۡهِم بِصِحَافٖ مِّن ذَهَبٖ وَأَكۡوَابٖۖ وَفِيهَا مَا تَشۡتَهِيهِ ٱلۡأَنفُسُ وَتَلَذُّ ٱلۡأَعۡيُنُۖ وَأَنتُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ٧١ وَتِلۡكَ ٱلۡجَنَّةُ ٱلَّتِيٓ أُورِثۡتُمُوهَا بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ٧٢ لَكُمۡ فِيهَا فَٰكِهَةٞ كَثِيرَةٞ مِّنۡهَا تَأۡكُلُونَ٧٣

66. Ba abin da suke jira sai alƙiyama kawai ta zo musu kwatsam, alhali ba tare da sun sani ba.

67. Masoya a wannan ranar maƙiyan juna ne sai masu taƙawa kaɗai.

68. Ya ku bayina, babu wani tsoro gare ku a yau, kuma ba za ku yi baƙin ciki ba.

69. (Su ne) waɗanda suka yi imani da ayoyinmu, suka kuma kasance Musulmi.

70. (Za a ce da su): ‘‘Ku shiga Aljanna ku da matanku, za a faranta muku rai.’’

71. Ana zagayawa tsakaninsu da akusa na zinari da kofuna; a cikinta kuma akwai (duk) abin da rayuka suke shaʾawa, idanuwa kuma suke jin daɗin (ganinsu); ku kuma a cikinta madawwama ne.

72. Waccan kuma ita ce Aljannar da aka gadar muku ita saboda abin da kuka kasance kuma aikatawa.

73. A cikinta kuna da ‘ya‘yan itatuwa na marmari masu yawa, daga gare su kuma za ku riƙa ci.
A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa duk masu ƙaryata manzannin Allah da haɗa shi da wasu ababen bauta, ba komai suke jira ba sai alƙiyama ta zo musu kwatsam ba zato ba tsammani. To idan har ta riske su suna cikin wannan kafircin nasu to makomarsu ita ce azabar Allah mai tsanani.

Sai kuma ya bayyana cewa duk wata abokantaka da soyayya za su rikiɗe a ranar alƙiyama su zama ƙiyayya, in ban da soyayyar da aka ƙulla ta don Allah, watau soyayyar masu taƙawa, wannan kam mai ɗorewa ce har abada.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Abubuwa uku wanda suka kasance tare da shi to ya samu ɗanɗanon imani; ya fi son Allah da Manzonsa fiye da komai; ya kuma so bawa ba don komai ba sai don Allah; ya kuma yi ƙyamar komawa cikin kafirci bayan Allah ya tserar da shi daga gare shi, kamar yadda yake ƙin a jefa shi cikin wuta." [Bukhari #21 da Muslim #43].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah a ranar alƙiyama zai ce: 'Ina masu soyayya domin girmana? A yau zan saka su cikin inuwata ranar da babu wata inuwa sai inuwata.'" [Muslim #2566].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa zai kirawo bayinsa a wannan ranar da siffar bayinsa masu daraja da cewa, babu wani tsoro da za su fuskanta a wannan ranar, kuma ba za su yi baƙin cikin abin da suka baro ba a duniya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta waɗannan bayi nasa da cewa, su ne waɗanda suka yi imani da ayoyinsa, watau Alƙur'ani mai girma, suka kuma kasance masu miƙa wuya a gare shi, suna aiki da karantarwarsa, suna bin umarninsa suna kuma guje wa haninsa.
A ranar za a umarci waɗannan bayi da su shiga Aljanna su da waɗanda suke ire-irensu masu ayyuka na ƙwarai irin nasu, kamar matayensu da 'ya'yansu da sauran makusantansu, inda za su sami farin ciki marar yankewa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani sashe na ni'imar da za a faranta musu rai da ita a gidan Aljanna, yayin da hadimansu za su riƙa zagayawa a tsakaninsu da akusa na zinare da kofunan zinare cike da abubuwan shaye-shaye. Kuma Allah ya tanadar musu duk abin da ransu yake sha'awa, idanuwansu kuma suke jin daɗin ganin sa a gidan Aljanna, ga shi kuma za su yi ta zama ne a cikinta har abada babu mai fitar da su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa wannan gida na Aljanna da yake cike da ni'imomi iri-iri shi ne wanda ya gadar musu da shi saboda kyawawan ayyukan da suka kasance suna aikatawa a duniya.
Ya kuma sanar da su cewa, a cikin Aljanna suna da 'ya'yan itatuwa na marmari masu yawa waɗanda ba sa yankewa, waɗanda za su riƙa ci. Watau bayan an ambaci abubuwan ci da na sha sai kuma aka ambaci kayan marmari domin a cika musu ni'ima da farin ciki.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba a sassauta wa kafirai azaba a cikin wuta ko kaɗan.

2. Kafirai masu dawwama ne a cikin wuta, ba su da ranar fita daga cikinta har abada.

3. Cikar adalcin Allah, ba ya azabtar da kowa sai wanda ya zalunci kansa da kafirci ko ayyukan saɓo.

4. Sunan shugaban mala'iku masu tsaron wuta Maliku.

5. Girman haɗarin ƙin gaskiya.

6. Makircin kafirai a kansu zai ƙare, ko badaɗe ko bajima.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da mala'iku masu rubuta ayyukan bayinsa, don tsayar musu da hujja a lahira, amma shi Allah ya riga ya san komai da komai.

Suratuz Zukhruf (74-80)

إِنَّ ٱلۡمُجۡرِمِينَ فِي عَذَابِ جَهَنَّمَ خَٰلِدُونَ ٧٤ لَا يُفَتَّرُ عَنۡهُمۡ وَهُمۡ فِيهِ مُبۡلِسُونَ ٧٥ وَمَا ظَلَمۡنَٰهُمۡ وَلَٰكِن كَانُواْ هُمُ ٱلظَّٰلِمِينَ ٧٦ وَنَادَوۡاْ يَٰمَٰلِكُ لِيَقۡضِ عَلَيۡنَا رَبُّكَۖ قَالَ إِنَّكُم مَّٰكِثُونَ ٧٧ لَقَدۡ جِئۡنَٰكُم بِٱلۡحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَكُمۡ لِلۡحَقِّ كَٰرِهُونَ ٧٨ أَمۡ أَبۡرَمُوٓاْ أَمۡرٗا فَإِنَّا مُبۡرِمُونَ ٧٩ أَمۡ يَحۡسَبُونَ أَنَّا لَا نَسۡمَعُ سِرَّهُمۡ وَنَجۡوَىٰهُمۚ بَلَىٰ وَرُسُلُنَا لَدَيۡهِمۡ يَكۡتُبُونَ ٨٠

74. Lalle masu manyan laifuka suna cikin azabar (wutar) Jahannama suna masu dawwama.

75. Ba a yanke musu ita (azabar), su kuwa masu yanke ƙaunar (fita) ne daga cikinta.

76. Ba Mu kuwa zalunce su ba, sai dai su ne suka kasance azzalumai.

77. Suka kuma yi kiran: "Ya (kai mai tsaron wuta) Maliku, Ubangijinka Ya kashe mu mana!" Ya ce: "Lalle ku masu dawwama ne."

78. Haƙiƙa Mun zo muku da gaskiya sai dai kuma mafiya yawanku masu ƙin gaskiya ne.

79. A'a, sun dai shirya wani makirci ne, Mu ma lalle Masu yin namu shirin ne.

80. Ko kuma suna tsammanin cewa Mu ba Ma jin asirinsu da ganawarsu ne? Ba haka ba ne, manzanninmu suna tare da su suna rubutawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon kafirai masu ƙaryata ayoyinsa, da cewa a ranar alƙiyama za su tsunduma cikin wutar Jahannama, za su kuma dawwama a cikinta har abada. Kuma ba za a sassauta musu azaba ba ko da ta yini ɗaya, sannan za su yanke ƙaunar samun wata rahamar Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa wannan azaba da ta same su ba Allah ne ya zalunce su ba, su ne suka zalunci kawunansu da aikata kafirci da saɓon Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa idan wuya ta yi wuya ga 'yan wuta za su riƙa kururuwa suna kiran Mala'ika Maliku mai tsaron wuta suna kamun ƙafa da shi a kan ya roƙa musu Allah ya karɓi ransu don su huta da tsananin azabar da suke ciki. Sai Maliku ya amsa musu da cewa haka za su yi ta zama cikin matsananciyar azaba har abada babu ƙaƙƙautawa. Daga nan sai ya daka musu tsawa yana mai tuna musu taurin kansu a duniya shi ne ya jawo musu wannan wahalar, domin mala'iku sun yi ta zuwa musu da gaskiya, watau wahayin da Mala'ika Jibrilu ya riƙa sauka da shi zuwa ga annabawa, to amma mafiya yawansu masu ƙin gaskiya ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin makircin da mushirikai suka yi ta ƙulla wa Manzonsa (ﷺ) yadda za su murƙushe gaskiya su kashe ta murus, to amma ba su san cewa shi ma Allah yana shirya nasa al'amarin ba ne wanda zai murƙushe makircinsu da mummunan shirinsu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi kafirai da cewa, shin suna zaton cewa ba ya jin abin da suke ɓoyewa a zukatansu na mugun nufi ko wanda suke ƙullawa yayin ganawarsu ta sirri? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, yana jin komai da suke ƙullawa, kuma mala'ikunsa suna tare da su suna rubuta duk wani motsinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Da a ce Allah yana da ɗa to da manzannin Allah su ne za su fara miƙa wuya a gare shi, domin sun fi kowa son Allah da yi masa biyayya sau da ƙafa, da kwaɗayin alheri da guje wa sharri. Don haka da a ce mala'iku 'ya'yan Allah ne, kamar yadda mushirikai suke da'awa, to da Annabi (ﷺ) shi ne farkon wanda zai bauta musu, saboda kamalar biyayyarsa ga Allah, da kuma mushirikai ba za su riga shi ba.

2. Ilimin mushirikai ba mai amfani ba ne, sai dai cutarwa, domin kutse ne cikin ƙarya, don neman abin da za su kore gaskiya da shi, su tabbatar da ƙarya, kuma ayyukan wasa ne ba su da wani amfani a gare su, domin ba za su tsarkake zukatansu ba, ba kuma za su amfane su a lahira ba.

Suratuz Zukhruf (81-83)
قُلْ إِن كَانَ لِلرَّحْمَٰنِ وَلَدٌ فَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلْعَٰبِدِينَ ﴿٨١﴾ سُبْحَٰنَ رَبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ رَبِّ ٱلْعَرْشِ عَمَّا يَصِفُونَ ﴿٨٢﴾ فَذَرْهُمْ يَخُوضُوا۟ وَيَلْعَبُوا۟ حَتَّىٰ يُلَٰقُوا۟ يَوْمَهُمُ ٱلَّذِى يُوعَدُونَ ﴿٨٣﴾

81. Ka ce: "Idan da (Allah) Mai rahma zai zamanto Yana da ɗa, to ni ne farkon masu bauta."

82. Tsarki ya tabbata ga Ubangijin sammai da ƙasa, Ubangiijn Al'arshi game da abin da suke siffantawa.

83. Sai ka bar su su yi ta kutse suna wasanni, har su haɗu da ranar da ake alƙawarta musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya faɗa wa mushirikai masu cewa, Allah yana da 'ya'ya mata watau mala'iku, cewa idan har za a ƙaddara cewa Allah mai rahama yana da ɗa, to ya tabbatar musu cewa shi ne farkon masu bauta wa wannan ɗan, domin kuwa zai zama wani sashi ne nasa. Shi kuma Manzon (ﷺ) Allah shi ne wanda ya fi kowa cancantar ya miƙa wuya ga abin da Allah yake so, to amma abin ba haka yake ba, Allah ba shi da ɗa, don haka Manzonsa (ﷺ) shi ne farkon masu musunta haka da kore wa Allah ɗa. Wannan shi ya tabbatar da ɓacin wannan aƙidar.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkake kansa daga duk wata tawaya ko aibu dangane da abin da mushirikai suke jingina masa na mata da 'ya'ya, domin kuwa shi ne Ubangijin sammai da ƙasa, Ubangijin Al'arshi mafi girman halittunsa.
Sai kuma Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya yi watsi da mushirikai da duk wani irin kutsen da suke yi cikin kafirci da saɓon Allah da wasanninsu na duniya har sai sun haɗu da ranar da ake yi musu alƙawarin zuwanta, watau ranar alƙiyama inda za su ga sakamakon munanan ayyukansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah ne kaɗai abin bauta na gaskiya a cikin sammai da kuma a ƙasa.

2. Babu wanda ya san ranar zuwan alƙiyama sai Allah kaɗai.

3. Babu wani mai ceto a lahira sai wanda ya yarda da Kalmar Shahada, ya kuma fahimci ma'anarta ya tabbatar da ita a aikace.

4. Mushirikan Larabawa na zamanin Manzon Allah (ﷺ) sun yarda da Tauhidin Rububiyya, watau kaɗaita Allah da ayyukansa, kamar yin halitta da arzutawa, amma wannan kaɗai bai shigar da su Musulunci ba, domin ba su yarda da Tauhidin Uluhiyya ba, watau kaɗaita Allah da bauta.

5. Duk wanda ya yi imani da Tauhidin Rububiyya, to ya zama dole ne a kansa ya yi imani da Tauhidin Uluhiyya, idan ba haka ba, to yana tufka ne da warwara.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da kada ya daka ta kafirai; ya riƙa mayar musu da magana mai kyau yayin da suka fuskance shi da mummunar magana ko suka yi nufin cutar da shi. Haka kuwa ta tabbata, domin Annabi (ﷺ) daga ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi gagarumar nasara a kansu, mutane suka yi ta shiga addinin Musulunci ƙungiya-ƙungiya.

Suratuz Zukhruf (84-89)

وَهُوَ ٱلَّذِى فِى ٱلسَّمَآءِ إِلَٰهٌ وَفِى ٱلْأَرْضِ إِلَٰهٌ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْعَلِيمُ ﴿٨٤﴾ وَتَبَارَكَ ٱلَّذِى لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا وَعِندَهُۥ عِلْمُ ٱلسَّاعَةِ وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٨٥﴾ وَلَا يَمْلِكُ ٱلَّذِينَ يَدْعُونَ مِن دُونِهِ ٱلشَّفَٰعَةَ إِلَّا مَن شَهِدَ بِٱلْحَقِّ وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿٨٦﴾ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَهُمْ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۖ فَأَنَّىٰ يُؤْفَكُونَ ﴿٨٧﴾ وَقِيلِهِۦ يَٰرَبِّ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ قَوْمٌ لَّا يُؤْمِنُونَ ﴿٨٨﴾ فَٱصْفَحْ عَنْهُمْ وَقُلْ سَلَٰمٌ ۚ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ﴿٨٩﴾

84. Shi ne kuma Wanda Yake Abin bauta a cikin sama kuma Abin bauta a ƙasa. Kuma Shi Mai hikima ne, Masani.

85. Kuma wanda Yake da mulkin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu alhairansa sun yi yawa, kuma a wurinsa sanin (ranar) alƙiyama yake, wurinsa kuma za a komar da ku.

86. Waɗanda kuwa suke bauta wa wani abu ba Shi ba, ba sa mallakar ceto, sai dai waɗanda suka yi Kalmar Shahada ta gaskiya, alhalin suna sane (da ma'anarta).|

87. Tabbas kuma da za ka tambaye su, wane ne ya halicce su? Lalle za su ce: "Allah ne;" to ta yaya ake kautar da su?

88. Kuma (sanin) faɗarsa (wato Ma'aiki) cewa: "Ya Ubangiji lalle waɗannan mutane ne da ba sa yin imani," (yana a wurinsa).

89. To ka kawar musu kai, kuma ka ce: "Na kuɓuta (daga haƙƙinku). Don haka ba da daɗewa ba za ku sani."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa shi ne kaɗai abin bauta na gaskiya a sama da kuma a ƙasa, kuma shi ne mai hikima a cikin halittarsa da Ƙaddararsa da tsarinsa; masanin halayen bayinsa da ayyukansu ne.
Kuma albarkatunsa sun yawaita, shi ne kaɗai mamallakin sammai da ƙasa da duk abin da yake tsakaninsu, kuma shi kaɗai ne ya san lokacin zuwan ranar alƙiyama, ranar da kowa da komai za a mayar da su zuwa gare shi, domin yin hisabi da sakamako.
Haka kuma ya tabbatar wa mushirikai cewa abubuwan da suke bauta wa ba Allah ba suna zaton za su cece su a wurinsa a ranar alƙiyama ba za su mallaki ceton kowa ba. Babu wanda zai yi ceto a ranar sai wanda ya shaida babu abin bauta da gaskiya sai Allah, yana kuma sane da ma'anar Kalmar Shahadar da ya yi, kamar Annabi Isa da Uzairu da mala'iku, waɗannan suna cikin masu ceto ga waɗanda suka mutu a kan Tauhidi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake bayyana wa Manzonsa (ﷺ) wata tufka da warwara ta kafirai masu barin bautar Allah mahalicci, su kama bautar waninsa, da cewa, da zai tambaye su, wane ne ya halicce su? Ba su da wata amsa da ta wuce su ce, Allah ne ya halicce su. To abin mamaki ta yaya ake kautar da su daga bautar Allah bayan sun yarda shi ne mahaliccinsu?

Daga nan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yana sane da koken da Manzonsa (ﷺ) yake kai masa na cewa, mutanensa sun ƙaryata shi, sun ƙi yin imani da abin da ya aiko shi zuwa gare su da shi.
A ayar ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya kawar da kansa daga gare su, ya faɗa musu abin da zai kare kansa daga sharrinsu, domin ba da daɗewa ba za su san uƙubar da za ta faru gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman darajar Alƙur'ani da darajar lokacin da aka saukar da shi.

2. An saukar da Alƙur'ani a dunƙule a karon farko a cikin daren Lailatul Ƙadari a sama ta farko, sannan aka saukar da shi guntu-guntu a tsawon shekara ashirin da uku.

3. Daren Lailatul Ƙadari dare ne mai cike da albarka.

4. A cikin daren Lailatul Ƙadari ake rubuta kuma a tantance duk wani al'amari na ƙaddara ko na shari'a da Allah ya riga ya hukunta. Wannan rubutu da tantancewa da za a yi a wannan dare daidai yake da abin da yake rubuce a littafin Lauhul-Mahfuz wanda ya ƙunshi komai da zai faru a duniya.

5. Babu wata rahama da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa bayinsa wadda ta fi manzanni da saukar da littattafai masu ƙunshe da shiriya ga ɗan'adam.

6. Yarda da imani da zamantowar Allah shi ne mahaliccin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, yana wajabta a kaɗaita shi wajen bauta kada a haɗa aiko komai da shi

44-Suratud Dukhan

Mabuɗin Sura:

1.Sunanta:
An fi sanin ta da sunan '*Suratud Dukhan*' kamar yadda yake a cikin littattafan tafsiri da hadisi.
Ad-DuKhan, yana nufin hayaƙi. Wato mu'ujizar da Allah ya karfafi Annabi Muhammadu (ﷺ) da ita, kuma Surar ta zo da bayaninta. Daga nan aka sami sunanta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Babu saɓani a tsakanin malamai a kan cewa Sura ce *Makkiyya*, watau an saukar da ita kafin hijirar Manzon Allah (ﷺ).

3.jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta sittin da uku (63) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratuz Zukhruf*' kafin '*Suratul Jasiya*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta hamsin da shida ne (56) a lissafin mutanen Madina da Makka da Sham. A lissafin mutanen Basra kuwa adadinsu hamsin da bakwai ne (57). Amma a wurin mutanen Kufa adadinsu hamsin da tara ne (59).

5. Babban Jigonta:
Tana jan hankalin kafirai ne zuwa ga tunani cikin lamarin Alƙur'ani da imani da tashin alƙiyama, ta hanyar tsoratarwa da gargaɗi da wa'azi da labaran al'ummun da suka gabata waɗanda Allah ya hallakar saboda ƙaryata mazanninsa da suka yi.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa

1.Kira zuwa ga girman darajar Alƙur'ani.

2. Bayani a kan cewa izgilin da mushirikai suka yi, shi ne ya hana su tsayawa su yi tunani game da gaskiyar da Manzo ya zo musu da ita.

3. Farkar da tunanin mushirikai game da haɗarin abin da suke kai na kafirci da ƙaryata Manzon Allah (ﷺ), ta hanyar jarrabar su da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi da amsa addu'ar Manzonsa (ﷺ), har aka jarrabe su da yunwa.

4. Bayanin misalan al'ummun da suka gabata waɗanda aka hallaka su saboda ƙaryata manzanninsu da suka yi.

5. Tabbatar da zuwan tashin alƙiyama wanda mushirikai suke ƙaryatawa.

6. Bayanin wasu manyan dalilai masu tabbatar da Kaɗaitakar Allah.

7. Lallashin zuciyar Manzon Allah (ﷺ) da bayyana masa cewa nasara tasa ce.

Suratud Dukhan (1-9)

حمٓ ۝١ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ۝٢ إِنَّآ أَنزَلۡنَٰهُ فِي لَيۡلَةٖ مُّبَٰرَكَةٍۚ إِنَّا كُنَّا مُنذِرِينَ ۝٣ فِيهَا يُفۡرَقُ كُلُّ أَمۡرٍ حَكِيمٍ ۝٤ أَمۡرٗا مِّنۡ عِندِنَآۚ إِنَّا كُنَّا مُرۡسِلِينَ ۝٥
رَحۡمَةٗ مِّن رَّبِّكَۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ۝٦ رَبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَآۖ إِن كُنتُم مُّوقِنِينَ ۝٧ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۖ رَبُّكُمۡ
وَرَبُّ ءَابَآئِكُمُ ٱلۡأَوَّلِينَ ۝٨ بَلۡ هُمۡ فِي شَكّٖ يَلۡعَبُونَ ۝٩

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ha Mim.

2. Na rantse da Littafi mai bayyanawa (shi ne Alƙur'ani).

3. Lalle Mu Muka saukar da shi a cikin dare mai albarka. Lalle Mu Mun kasance Masu gargaɗi.

4. A cikinsa ne (daren) ake fasalta kowane tabbataccen al'amari (na wannan shekara).

5. Al'amari ne (da Muke fasaltawa) daga wurinmu. Lalle Mun kasance Mu ne Masu aikowa (da manzanni).

6. Don rahama daga Ubangijinka. Lalle shi Mai ji ne, Masani.

7. Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu; idan kun kasance masu sakankancewa.

8. Babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi, Shi ne Yake rayarwa Yake kuma kashewa; (Shi ne) Ubangijinku kuma Ubangijin iyayenku na farko.

9. A'a, su dai suna cikin shakka ne, suna wasanni.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da wasu haruffa kamar yadda a baya ya buɗe wasu surori da irinsu. [Dubi bayaninsu a farkon tafsirinmu na *Suratul Baƙara*].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da Alƙur'ani wanda yake ɗauke da bayanin hanyar shiriya mai kaiwa zuwa gaskiya. Ya kuma tabbatar da cewa shi ne ya saukar da wannan Alƙur'anin a cikin wani dare mai albarka, shi ne daren Lailatul Kadari, wanda yake dare ne mai cike da alherai.
Sai kuma ya bayyana hikimar saukar da shi da cewa, Allah shi ne mai gargaɗin mutane, ta hanyar nuna musu abin da zai amfane su da sanar da su abin da zai cutar da su, domin hujjarsa ta kafu a kan kowa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sirrin da ke cikin wannan daren na Lailatul Kadari da ya zaba don saukar da Alƙur'ani a cikinsa, inda ya ambaci cewa a cikinsa ne ake tantance dukkan tabbatattun al'amura waɗanda suka shafi rabon arziƙi da tsawon rai da sauran abubuwa da Allah ya hukunta za su faru a wannan shekarar.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa wannan wani al'amari ne daga wajensa, babu wanda ya isa ya canja shi ko ya kawar da shi, sannan mutane su sani cewa shi ne mai aiko da manzanni zuwa gare su

don su karanta musu ayoyinsa. Ya kuma yi haka ne don rahama daga gare shi ga bayinsa domin su rarrabe tsakanin shiriya da ɓata, saboda shi mai jin maganganun bayinsa ne, masanin ayyukansu, don haka shi ya fi sanin abin da ya dace da su a rayuwarsu ta duniya da ta lahira.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kaɗaitakarsa a kan halittar sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu da iko da su, don haka idan mutane sun sakankance da haka, to lallai su yi imani da shi su bi Manzonsa (ﷺ) da ya aiko.
Allah kuma ya tabbatar musu cewa shi ne kaɗai abin bauta na gaskiya, domin shi kaɗai ne mai rayawa mai kashewa, shi ne kuma Ubangijinsu kuma Ubangijin iyayensu na farko.
To amma kuma su waɗannan mushirikai ba su sakankance da hakan ba, don haka suna cikin shakka, wasannin banza sun ɗauke musu hankali sun gafala daga tunanin manufar da ta sa aka halicce su, watau don bautar Allah shi kaɗai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gaggawar amsar addu'ar Annabi (ﷺ).

2. Tsaurin kan kafirai da rashin cika alƙawarinsu.

3. Mutane sukan tuba su kama hanyar gaskiya yayin da dalilai suka bayyana gare su, ko kuma yayin da suka ga wata azaba ta nufo su. Kafiran Makka sun ga dalilai masu yawa da ke nuna gaskiyar Annabi (ﷺ) da ingancin manzancinsa, amma ba su yi imani ba. Sai aka nuna musu aya ta jarraba da wata musiba, amma duk da haka yawancinsu ba su saduda sun miƙa wuya ba.

4. Ranar yaƙin Badar rana ce da Allah ya damƙi manyan kafiran Makka saboda butulcinsu da kafircinsu.

Suratud Dukhan (10-16)
فَٱرۡتَقِبۡ يَوۡمَ تَأۡتِي ٱلسَّمَآءُ بِدُخَانٖ مُّبِينٖ ١٠ يَغۡشَى ٱلنَّاسَۖ هَٰذَا عَذَابٌ أَلِيمٞ ١١ رَّبَّنَا ٱكۡشِفۡ عَنَّا ٱلۡعَذَابَ إِنَّا مُؤۡمِنُونَ ١٢ أَنَّىٰ لَهُمُ ٱلذِّكۡرَىٰ وَقَدۡ جَآءَهُمۡ رَسُولٞ مُّبِينٞ ١٣ ثُمَّ تَوَلَّوۡاْ عَنۡهُ وَقَالُواْ مُعَلَّمٞ مَّجۡنُونٌ ١٤ إِنَّا كَاشِفُواْ ٱلۡعَذَابِ قَلِيلًاۚ إِنَّكُمۡ عَآئِدُونَ ١٥ يَوۡمَ نَبۡطِشُ ٱلۡبَطۡشَةَ ٱلۡكُبۡرَىٰٓۚ إِنَّا مُنتَقِمُونَ ١٦

10. Sai ka saurari ranar da sama za ta zo da hayaƙi bayyananne.

11. Zai lulluɓe (idanuwan) mutane; wannan azaba ce mai raɗaɗi.

12. (Za su ce): "Ya Ubangijinmu, Ka yaye mana wannan azaba, lalle mu masu yin imani ne."

13. Ta ina wa'azi zai amfane su, alhali kuwa haƙiƙa Manzo mai bayani ya zo musu?

14. Sannan suka juya masa baya suka ce: "Ai wani ne ya koya masa, (kuma shi) taɓaɓɓe ne.

15. Lalle Mu Masu yaye muku azabar ne ɗan lokaci kaɗan. Lalle (kuma) ku masu komawa ne.

16. (Ka tuna) ranar da za Mu damƙe su babbar damƙa, lalle Mu Masu sakawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) tare da kakkausan jan kunne ga mushirikai masu ƙaryata shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya jira zuwan wata azaba ta

kurkusa ga mutanensa, ranar da sama za ta zo da wani hayaƙi wanda idanuwansu za su riƙa nuna musu shi saboda tsananin yunwa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan azaba za ta lulluɓe mutanensa, a lokacin za a riƙa faɗa musu cewa wannan azaba ce mai raɗaɗi.
Sai su kuma suna masu ƙasƙantar da kai ga Allah suna roƙon sa ya yaye musu azabar da suke ciki sun yi masa alƙawarin za su yi imani da shi da Manzonsa.
To amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san alƙawarinsu na banza ne ba cikawa za su yi ba, domin kuwa ta yaya za su wa'azantu su koma ga Allah alhali ga Manzo ya zo musu yana bayyana musu saƙon Allah a fili, sun kuma san gaskiyarsa da amanarsa amma suka ƙi yin imani da shi, suka ma juya masa baya suna zargin sa da cewa Alƙur'ani da yake karanta musu wani ne ya koya masa ba wahayi ne daga Allah ba, kuma shi mai taɓin hankali ne. Sai yanzu ne za su yi alƙawarin cewa za su yi imani da shi?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa lalle shi zai yaye musu azabar zuwa wani ɗan lokaci, to amma ya san ba za su cika alƙawarinsu ba; za su sake komawa ga laifukansu ne.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da su cewa idan wannan gargaɗin da azabar ba ta yi musu amfani ba, to su jira ranar da Allah zai damƙe su kyakkyawar damƙa, ita ce ranar yaƙin Badar, lalle a ranar Allah sai ya yi musu azabar ramuwa saboda kafircinsu ga Allah da Manzonsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da Kuraishawa suka tirje suka ƙi karɓar Musulunci daga hannun Annabi (ﷺ), sai ya roƙi Allah ya jarrabe su da fari da yunwa irin ta zamanin Annabi Yusuf (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Sai kuma Allah ya karɓi addu'arsa, aka jarrabe su da ƙunci da yunwa har ta kai suna cin ƙasusuwa da mushen dabba. Idan sun ɗaga kansu sama ba abin da suke gani sai hayaƙi saboda tsananin yunwa. Sai Abu Sufyana ya je ya sami Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Ya Muhammadu, kai ne kake umarni da a yi wa Allah biyayya da sada zumunci, to amma kana gani ga mutanenka nan suna ta mutuwa, ka roƙa musu Allah mana ya yaye musu halin da suke ciki?" [Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyin daga farkon aya ta 10 zuwa ta 16]. [Bukhari #1007 da Muslim #2798].

A wata ruwayar: Annabi (ﷺ) ya yi musu addu'a sai aka samu ruwan sama mai yawa har tsawon mako guda ba ƙaƙƙautawa har sai da mutane suka fara kokawa da yawan ruwan, sannan Manzon Allah (ﷺ) ya yi addu'ar a janye musu shi daga cikin gari zuwa bayan gari. [Bukhari #1020].

Daga baya kuma suka ci gaba da kafircinsu da muzguna wa Manzon Allah (ﷺ) sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu mummunar damƙa a yaƙin Badar inda aka kashe manya-manyansu. [Dubi, Bukhari #4822].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa mushirikan Kuraishawa cewa, duk abin da suke taƙama da shi na ƙarfi da dukiya, to Fir'auna da mutanensa sun zarce su, amma duk da haka Allah ya hallaka su lokacin da suka ƙaryata Manzonsa Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka yi ƙoƙarin cutar da shi, don haka su ma ba su fi ƙarfin Allah ya yi musu haka ba.

2. Duk wani manzo da Allah ya aiko mutum ne mai daraja da mutunci a cikin mutanensa tun gabanin a ba shi annabta.

3. Yana daga cikin manufofin annabawan Allah su 'yanta masu rauni daga ƙangin bautar azzalumai.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga Fir’auna don ya kira shi zuwa ga imani da Allah ya kuma saki Banu Isra’ila da yake ɗaure da su. Yayin da ya bijire wa yin imani sai Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya neme shi da ya saki Banu Isra’ila ya fita harkarsa ya ƙyale shi.

5. Amana siffa ce muhimmiya ga manzannin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. A kowane lokaci idan azzalumai suka ga ƙaryarsu ta ƙare, sai su shiga barazanar ɗaukar matakin kisa ko ɗauri.

7. Neman tsari daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) game da duk wani mai nufin sharri ga masu kira zuwa ga Allah.

Suratud Dukhan (17-24)
*وَلَقَدۡ فَتَنَّا قَبۡلَهُمۡ قَوۡمَ فِرۡعَوۡنَ وَجَآءَهُمۡ رَسُولٞ كَرِيمٌ ١٧ أَنۡ أَدُّوٓاْ إِلَيَّ عِبَادَ ٱللَّهِۖ إِنِّي لَكُمۡ رَسُولٌ أَمِينٞ ١٨ وَأَن لَّا تَعۡلُواْ عَلَى ٱللَّهِۖ إِنِّيٓ ءَاتِيكُم
بِسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٖ ١٩ وَإِنِّي عُذۡتُ بِرَبِّي وَرَبِّكُمۡ أَن تَرۡجُمُونِ ٢٠ وَإِن لَّمۡ تُؤۡمِنُواْ لِي فَٱعۡتَزِلُونِ ٢١ فَدَعَا رَبَّهُۥٓ أَنَّ هَٰٓؤُلَآءِ قَوۡمٞ مُّجۡرِمُونَ ٢٢ فَأَسۡرِ
بِعِبَادِي لَيۡلًا إِنَّكُم مُّتَّبَعُونَ ٢٣ وَٱتۡرُكِ ٱلۡبَحۡرَ رَهۡوًاۖ إِنَّهُمۡ جُندٞ مُّغۡرَقُونَ ٢٤

17. Haƙiƙa kuma Mun jarrabi mutanen Fir’auna tun kafin su, kuma Manzo mai karamci ya zo musu.

18. (Da cewa): “Ku ba ni bayin Allah (watau Banu Isra’ila); lalle ni Manzo ne amintacce a gare ku.

19. “Kuma kada ku yi wa Allah girman kai; lalle ni zan kawo muku hujjoji mabayyana.

20. “Kuma lalle ni ina neman tsari na Ubangijina kuma Ubangijinku, don kada ku jefe ni.

21. “Idan kuma ba ku yi imani da ni ba sai ku ƙyale ni.”

22. Sai ya roƙi Ubangijinsa cewa: “Lalle waɗannan mutane ne masu manyan laifuka.”

23. Sai (aka ce masa): “Ka tafi da bayina da daddare, lalle ku za a biyo bayanku.24. “Kuma ka bar ƙogi a tsaye cak (bayan tsallakewa); lalle su runduna ne da za a nutsar.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Manzonsa (ﷺ) cewa ba shi ne farkon Annabin da mutanensa suka ƙaryata ba, akwai waɗanda suka gabace shi da yawa waɗanda mutanensu suka ƙaryata su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa cewa, a can baya ya jarrabi mutanen Fir’auna ya aika musu Manzonsa mai karamci, watau Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Yayin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya je wa Fir’auna da mutanensa sai ya neme su da su sakar masa bayin Allah waɗanda suke tsare da su suna gana musu azaba ba don sun yi musu wani laifi ba sai don zalunci, su ne Banu Isra’ila da ke ɗaure a wurin Fir’auna. Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya tabbatar musu da cewa shi Manzon Allah ne amintacce zuwa gare su, ba zai ƀoye musu komai daga saƙon Allah ba, ba kuma zai ƙara ko ya rage ba.
Ya gargaɗe su cewa, kada su kuskura su ce za su yi wa Allah girman kai su ci gaba da kafirce masa da zaluntar bayinsa, ya tabbatar musu da cewa, zai zo musu da hujja bayyananna mai tabbatar da gaskiyarsa.
To amma sai Fir’auna da mutanensa suka ƙaryata Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), suka fara tunanin kashe shi, sai ya koma ga Allah ya nemi tsarinsa daga sharrinsu don kada su jefe shi har lahira.

Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nemi ɗayan abubuwa biyu daga gare su: Na farko, su yi imani da shi, na biyu, idan ba za su yi imani da shi ba, to su ƙyale shi su fita harkarsa kada su yi tunanin cutar da shi. To amma sai ya rasa ko ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa biyu, sai ma suka fara yunƙurin hallaka shi har da mutanensa da suka yi imani da shi. A nan ne Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙi Ubangijinsa cewa Fir'auna da jama'arsa mutane ne masu manyan laifuka, sun cancanci a gaggauto musu da uƙuba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amsa roƙonsa ya umarce shi da ya fita shi da mutanensa su gudu cikin dare, lalle Fir'auna da rundunarsa za su biyo bayansu.
Haka kuwa ya faru, yayin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fita da Banu Isra'ila kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi, sai Fir'auna da rundunarsa suka bi bayansu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bugi kogi da sandarsa, nan take kuwa kogin ya dare ya yi hanyoyi har goma sha biyu, Annabi Musa da jama'arsa suka tsallaka suka wuce. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya bar kogin yadda yake don Fir'auna da mutanensa su ma su shiga cikinsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) cewa Fir'auna da rundunarsa duk za su nutse cikin ruwan. Haka kuwa ya faru, Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da jama'arsa suna gama fita shi kuma Fir'auna da rundunarsa sun gama shiga cikinsa sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci kogin ya haɗe da su, nan take duk suka nutse suka hallaka, ba ko mutum ɗaya daga cikinsu da ya tsira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samun ni'imar duniya ga kafiri ba ya nuna yana da wani matsayi a wurin Allah.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana canja ni'imar da ya yi wa mutane idan ba su tsaya da gode masa ba.

3. Azzalumai wulaƙantattun mutane ne, ƙasƙantattu a wurin Allah da muminai da duk sauran halittun Allah.4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan jarrabi bayinsa da ni'ima, kamar yadda yake jarrabar su da musiba.

Suratud Dukhan (25-33)
كَمْ تَرَكُواْ مِن جَنَّٰتٖ وَعُيُونٖ ٢٥ وَزُرُوعٖ وَمَقَامٖ كَرِيمٖ ٢٦ وَنَعۡمَةٖ كَانُواْ فِيهَا فَٰكِهِينَ ٢٧ كَذَٰلِكَۖ وَأَوۡرَثۡنَٰهَا قَوۡمًا ءَاخَرِينَ ٢٨ فَمَا بَكَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلسَّمَآءُ وَٱلۡأَرۡضُ وَمَا كَانُواْ مُنظَرِينَ ٢٩ وَلَقَدۡ نَجَّيۡنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ مِنَ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡمُهِينِ ٣٠ مِن فِرۡعَوۡنَۚ إِنَّهُۥ كَانَ عَالِيٗا مِّنَ ٱلۡمُسۡرِفِينَ ٣١ وَلَقَدِ ٱخۡتَرۡنَٰهُمۡ عَلَىٰ عِلۡمٍ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ٣٢ وَءَاتَيۡنَٰهُم مِّنَ ٱلۡأٓيَٰتِ مَا فِيهِ بَلَٰٓؤٞاْ مُّبِينٌ ٣٣

25. Sun bar gonaki da kuma idanuwan ruwa masu yawa.

26. Da kuma shuke-shuke da wurin zama mai daraja.

27. Da kuma kayan jin daɗi da suka kasance masu ni'imtuwa da su.

28. Kamar haka ne; sai Muka kuma gadar da su ga wasu mutane daban (su ne Banu Isra'ila).

29. Sannan (halittun) sama da na ƙasa ba su yi alhininsu ba, ba su kuma kasance ababen saurara wa ba.

30. Haƙiƙa kuma Mun tserar da Banu Isra'ila daga azabar wulaƙanci.

31. Daga Fir’auna. Lalle shi ya kasance mai girman kai daga maɓarnata.

32. Kuma haƙiƙa Mun fifita su (Banu Isra’ila) bisa saninmu a kan (sauran) talikai.

33. Muka kuma ba su wasu ayoyinmu waɗanda a cikinsa akwai jarrabawa mabayyaniya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin irin dangogin ni’ima da jin daɗin rayuwar duniya da Fir’auna da mutanensa suka bari bayan an dulmiyar da su cikin ruwa, da cewa sun bar gonaki da idanuwan ruwa masu yawa da shuke-shuke da majalisi na alfarma da kuma wata rayuwa ta jin daɗi da suke ciki.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa haka al’amarin ya faru da su kamar yadda aka yi bayani, kuma ya gadar wa Banu Isra’ila duk abubuwan can da aka bari na more rayuwa da gonaki da idanuwan ruwa.
Bayan Allah ya hallaka su gaba ɗayansu babu wani mahaluƙi da ya nuna baƙin ciki ko alhini a kansu, har sama da ƙasa ba su nuna damuwarsu a kan abin da ya same su ba, domin kuwa sun cancanci uƙubar da aka yi musu, don haka ma ko saurara musu ba a yi ba ballantana su tuba a karɓi tubansu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Banu Isra’ila irin ni’imar da ya yi musu yayin da ya tserar da su daga azabar wulaƙanci wadda Fir’auna da mutanensa suke ɗandana musu, lokacin da suka riƙa kashe musu ‘ya’ya maza suna barin mata, Allah ya hallaka musu Fir’auna da jama’arsa, domin shi mai girman kai ne kuma yana daga cikin maɓarnata masu ƙetare iyakokin Allah da addininsa.
Allah kuma ya tabbatar wa Banu Isra’ila cewa, ya zaɓe su bisa sani da cancanta ya kuma fifita su a kan sauran al’ummun zamaninsu, saboda yawan annabawansu.
Hakanan daga dalilai da ayoyi da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabi Musa don ƙarfafar sa akwai ni’ima ta sarari ga Banu Isra’ila, kamar *al-mannu da tsuntsayen salwa* da makamantansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

5. Mushirikan Makka sun kasance suna ƙaryata tashin alƙiyama, don haka duk wani bayani game da azabar lahira ba ya razana su, don ba su yarda za ta zo ba.

6. Hujjar kafirai ta ƙaryata tashi bayan mutuwa hujjar banza ce, domin an yi musu alƙawarin tashi ne bayan ƙarewar rayuwar duniya gaba ɗaya domin yi musu hisabi da sakamako, su kuma suna son a tayar musu da iyayensu da suka mutu tun kafin zuwan lokacin tashin alƙiyama. Sannan kuma ƙarfafan dalilai masu yawa da ke tabbatar da gaskiyar Manzon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sun bayyana a gare su.

7. Larabawan Makka sun yarda da cewa, ƙabilun Larabawan Himyar da Saba’i sun fi su komai na ƙarfi da mulki da jin daɗin duniya, domin suna yawace-yawace a cikin ƙasar Yaman suna ganin abubuwan da waɗancan ƙabilu suka bari. Waɗannan ƙabilu na Himyar da Saba’i su ne ake kira da mutanen Tubba’u. Tubba’u kuma laƙabi ne da ake kiran duk wanda ya yi sarautar ƙasar Yaman da shi.

Suratud Dukhan (34-37)
إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَيَقُولُونَ ﴿٣٤﴾ إِنۡ هِيَ إِلَّا مَوۡتَتُنَا ٱلۡأُولَىٰ وَمَا نَحۡنُ بِمُنشَرِينَ ﴿٣٥﴾ فَأۡتُواْ بِـَٔابَآئِنَآ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ﴿٣٦﴾ أَهُمۡ خَيۡرٌ أَمۡ قَوۡمُ تُبَّعٖ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ أَهۡلَكۡنَٰهُمۡۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ مُجۡرِمِينَ ﴿٣٧﴾

34. Lalle waɗannan (kafiran Makka) tabbas suna cewa:

35. “Babu wata mutuwa da za mu yi sai mutuwarmu ta farko, kuma mu ba za a tashe mu ba.

36. “To ku zo mana da iyayenmu idan kun kasance masu gaskiya.”

37. Yanzu su ne suka fi ko kuwa mutanen Tubba’u da waɗanda suke a gabaninsu? Duk Mun hallakar da su. Lalle sun kasance masu manyan laifuka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunar aƙidar nan ta kafirai ta rashin yarda da ranar alƙiyama, da cewa suna musunta tashi bayan mutuwa don suna ganin bayan rayuwarsu ta duniya babu sauran wata rayuwa daban, don haka idan sun mutu shi kenan babu tashi ko wani hisabi. Har ma suna ƙalubalantar Manzon Allah (ﷺ) da muminai da cewa, idan da gaske ne ana dawowa bayan mutuwa, to su dawo musu da iyayensu da suka riga suka mutu, tunda sun yarda Allah yana tashin matattu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu su ba su isa komai ba idan ya yi niyyar hallaka su ba za su gagare shi ba, domin kuwa ba su kai mutanen Tubba’u ba da wasu kafirai da suka gabace su, kamar Adawa da Samudawa; dukkansu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su yayin da suka ƙaryata manzanninsa, don haka su ma waɗannan mushirikan Allah yana iya hallaka su don kuwa lalle sun tabbata mutane ne masu manyan laifuka kamar waɗancan kafiran.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hikimar halittar sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, watau tabbatar da gaskiya. Shi ne bautar Allah shi kaɗai ba tare da haɗa shi da komai ba da bin shari’arsa da ya aiko annabawa da ita.

2. Yawancin mutane ba su san hikimar halittarsu a bayan ƙasa ba.

3. Ranar alƙiyama rana ce da Allah zai tattara dukkan halittunsa a cikinta domin yi musu hisabi da sakamako.

4. Babu mai iya amfanar wani a ranar alƙiyama sai wanda Allah ya ji ƙansa, saboda kyawawan ayyukansa da ya yi a duniya.

Suratud Dukhan (38-42)

وَمَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا لَٰعِبِينَ ٣٨ مَا خَلَقۡنَٰهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٣٩ إِنَّ يَوۡمَ ٱلۡفَصۡلِ مِيقَٰتُهُمۡ أَجۡمَعِينَ ٤٠ يَوۡمَ لَا يُغۡنِي مَوۡلًى عَن مَّوۡلَىٰ شَيۡـٔٗا وَلَا هُمۡ يُنصَرُونَ ٤١ إِلَّا مَن رَّحِمَ ٱللَّهُۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ٤٢

38. Ba Mu kuma halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu don wasa ba.

39. Ba Mu halicce su ba sai don gaskiya, sai dai kuma yawancinsu ba su san haka ba.

40. Lalle ranar alƙiyama ne lokacin da aka ƙayyade musu gaba ɗaya.

41. Ranar da wani masoyi ba zai amfana wa masoyinsa komai ba, su kuma ba za a taimaka musu ba.

42. Sai fa wanda Allah Ya ji ƙan sa. Lalle Shi ne Mabuwayi, Mai rahama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikar Kudurarsa da girman ikonsa da kamalar hikimarsa, da cewa bai halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu domin wasa ba, ko hakanan kara-zube ba don wata manufa ba. Ya tabbatar da cewa ya halicce su ne don gaskiya, watau a bauta masa shi kaɗai ba tare da an haɗa shi da komai ba, kuma ya umarci mutane ya hana su don yi musu sakayya a kan ayyukansu, to amma yawancinsu ba su san haka ba, don haka ne ba sa tunani dangane da halittar sammai da ƙasa da ma kawunansu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa ranar alƙiyama wadda a cikinta ne zai rarrabe tsakanin halittunsa rana ce da aka sanya musu lokacin zuwanta da Allah zai tara su a cikinta baki ɗaya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta ta da cewa, rana ce da wani makusanci ba zai amfana wa makusancinsa komai ba, kuma babu wasu da za su kare musu azabar Allah a ranar, domin mulki gaba ɗaya a ranar na Allah ne babu mai iya yin wani abu sai da izininsa. Sai dai wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ji ƙansa daga cikin mutane, to wannan shi ne zai amfana da kyawawan ayyukansa da ya gabatar a duniya, domin Allah mabuwayi ne wanda babu mai iya rinjayar sa, mai hikima ne cikin halittarsa da tsarinsa da shari'arsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin wani mummunan ɓangare na abincin 'yan wuta.

2. Tsakiyar wutar Jahannama yana daga cikin inda ya fi ko'ina tsananin zafi a cikinta.

3. Azabar kafiri a ranar alƙiyama ba ta taƙaita a kan gangar jikinsa kaɗai ba; sai ya ga wulaƙanci iri daban-daban da baƙar magana.

Suratud Dukhan (43-50)
إِنَّ شَجَرَتَ ٱلزَّقُّومِ ﴿٤٣﴾ طَعَامُ ٱلۡأَثِيمِ ﴿٤٤﴾ كَٱلۡمُهۡلِ يَغۡلِي فِي ٱلۡبُطُونِ ﴿٤٥﴾ كَغَلۡيِ ٱلۡحَمِيمِ ﴿٤٦﴾ خُذُوهُ فَٱعۡتِلُوهُ إِلَىٰ سَوَآءِ ٱلۡجَحِيمِ ﴿٤٧﴾ ثُمَّ صُبُّواْ فَوۡقَ رَأۡسِهِۦ مِنۡ عَذَابِ ٱلۡحَمِيمِ ﴿٤٨﴾ ذُقۡ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡكَرِيمُ ﴿٤٩﴾ إِنَّ هَٰذَا مَا كُنتُم بِهِۦ تَمۡتَرُونَ ﴿٥٠﴾

43. Lalle itaciyar Zaƙƙumu.

44. Abincin mai babban zunubi ce.

45. (Kuma) kamar narkakkiyar darma, tana tafarfasa a cikin ciki.

46. Kamar tafasar ruwan zafi.

47. (Za a ce da mala'iku): "Ku kama shi sannan ku ja shi tsakiyar wutar Jahima.

48. "Sannan ku kwarara azabar ruwan zafi a tsakiyar kansa,."

49. (Sai a ce da shi): "Ɗanɗana, lalle kai ɗin nan kai babban mutum ne mai daraja.

50. (Za a ce da kafirai): "Lalle wannan ne abin da kuka kasance kuna shakkar sa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana munanan sakamakon ‘yan wuta a ranar alƙiyama, da cewa, bishiyar Zaƙkum wadda take tsirowa a tsakiyar wutar Jahannama, ita ce abincin duk wani kafiri mai babban laifi; za a ciyar da shi munanan ‘ya’yanta waɗanda za su riƙa tafarfasa a cikin cikin ‘yan wuta, kamar tafasar narkakken baƙin mai ko tafasar ruwan da ya kai matuƙa wajen zafi.
Sai kuma a umarci mala’iku zabaniyawan wuta da cewa, su kama wannan kafiri su ja shi da ƙarfi da tsanani zuwa tsakiyar Jahannama, sannan su kwarara masa azabar tafasasshen ruwan zafi a kansa, ya yi ta ɗanɗanar azaba babu ƙaƙƙautawa.
Sannan cikin izgili da ba’a a riƙa faɗa masa cewa, ya ɗanɗani kuɗarsa, ai lalle shi babban mutum ne mai daraja a cikin mutanensa, kamar yadda ya kasance yana ɗaukar kansa a duniya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa kafirai cewa, wannan azabar ita ce abin da suka kasance suna shakkar aukuwarta domin ba su yi imani da ranar alƙiyama ba, to yau ga shi sun gani da idanuwansu babu kuma sauran shakka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Aljanna ce sakamakon masu taƙawa daga cikin bayin Allah.

2. Ni’imomin gidan Aljanna ba sa yankewa har abada.

3. Babban rabo shi ne kuɓuta daga shiga wuta da samun shiga Aljanna.

4. Samun shiga gidan Aljanna falala ce daga Allah ga bawansa mumini.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sauƙaƙe lafuzan Alƙur’ani da ma’anoninsa ga bayinsa.

Suratud Dukhan (51-59)
إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي مَقَامٍ أَمِينٖ ۝٥١ فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٖ ۝٥٢ يَلۡبَسُونَ مِن سُندُسٖ وَإِسۡتَبۡرَقٖ مُّتَقَٰبِلِينَ ۝٥٣ كَذَٰلِكَ وَزَوَّجۡنَٰهُم بِحُورٍ عِينٖ ۝٥٤ يَدۡعُونَ فِيهَا بِكُلِّ فَٰكِهَةٍ ءَامِنِينَ ۝٥٥ لَا يَذُوقُونَ فِيهَا ٱلۡمَوۡتَ إِلَّا ٱلۡمَوۡتَةَ ٱلۡأُولَىٰۖ وَوَقَىٰهُمۡ عَذَابَ ٱلۡجَحِيمِ ۝٥٦ فَضۡلٗا مِّن رَّبِّكَۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ۝٥٧ فَإِنَّمَا يَسَّرۡنَٰهُ بِلِسَانِكَ لَعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ۝٥٨ فَٱرۡتَقِبۡ إِنَّهُم مُّرۡتَقِبُونَ ۝٥٩

51. Lalle masu taƙawa suna cikin wani amintaccen wuri.

52. Cikin lambuna da idanuwan ruwa.

53. Suna saye da tufafi na alharini mai shara-shara da mai kauri suna fuskantar juna.

54. Kamar haka ne, Muka kuma aura musu (‘yan matan) Hurul-Ini.

55. A cikinta (Aljannar) suna kiran a kawo musu duk wani kayan marmari, suna cikin aminci.

56. Ba za su ɗanɗani wata mutuwa a cikinta ba sai dai mutuwar farko; Ya kuma tserar da su daga azabar wutar Jahima.

57. (Wannan) falala ce daga Ubangijinka. Wannan shi ne babban rabo

58. To kawai Mun sauƙaƙe shi ne (wato Alƙur’ani) da harshenka, don su wa’azantu.

59. To ka saurara, lalle su ma masu sauraro ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon masu taƙawa waɗanda suke kiyaye dokokinsa ta hanyar aikata abin da aka umarce su da barin abin da aka hana su, da cewa a ranar alƙiyama suna da wani wurin zama amintacce inda babu wani abin ƙi da zai same su. Wannan wuri kuwa shi ne gidajen Aljanna masu idanuwan ruwa da ke gudana a cikinsu. Tufafin da za su riƙa sawa kuma na alhariri ne mai shara-shara da mai kauri, suna zaune a kan kujeru suna fuskantar juna.
Bugu da ƙari kuma zai aura musu ‘yan matan *Hurul-Ini* masu tsananin kyau da manyan idanuwa masu tsananin fari da baƙi.
A cikin Aljannar za su riƙa kiran masu yi musu hidima don su kawo musu kayan marmari iri-iri da suke da buƙata, hankalinsu kwance ba sa fargabar cewa wannan jin daɗin nasu zai yanke, ko wata cuta za ta same su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa za su zauna a cikin wannan ni’imar har abada ba za su sake ɗanɗanar wata mutuwa ba sai wadda suka riga suka ɗanɗana ta farko a rayuwarsu ta duniya, sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsare su daga faɗawa cikin azabar Jahannama. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu wannan tagomashi ne don falala da kyautatawa daga gare shi. Allah ya tabbatar da cewa wannan shi ne babban rabo wanda babu kamarsa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Babu wanda aikinsa ne zai shigar da shi Aljanna.” Sai sahabbai suka ce: “Har kai ma ya Manzon Allah?” Ya ce: “Har ni ma, sai dai idan Allah ya lulluɓe ni da falalarsa da rahamarsa….” [Bukhari #5673 da Muslim #2816].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rufe Surar da tunatar da su ni’imar saukar da Alƙur’ani da harshen Larabci da kuma tsoratar da su mummunan ƙarshen masu ƙaryata gaskiya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, ya sauƙaƙe masa Alƙur’ani ta hanyar saukar masa da shi cikin harshensa na Larabci, domin mutanensa su fahimci saƙonsa su wa’azantu.
Sannan Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya ƙara haƙuri, ya saurari lokacin zuwan nasarar da ya yi masa alƙawarin zuwanta; su ma masu laifi lallai suna sauraron lokacin hallakarsu ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

6. Girman darajar Alƙur’ani da babban matsayinsa.

7. Alƙur’ani cike yake da hikima cikin duk abin da ya zo da shi na ilimi da tarbiyya, domin shi magana ce ta Allah wanda ya siffanta da cikakkiyar hikima cikin dukkan al’amuransa.

8. Farkon matakin gane ayoyin Allah da ɗaukar izina daga gare su shi ne, bawa ya yi imani da Allah imani cikakke, to duk sanda bawa mumini ya ƙara yin zuzzurfan bincike cikin halittun Allah, sai imaninsa ya riƙa ƙaruwa yana hauhawa, har ya kai mataki na sakankancewa, sannan kuma yana ƙara nutsawa cikin bincike da nazari cikin ayoyin Allah yana ƙara samun fahimta da hankaltar al’amura yadda suke, har ya kai ga isa mataki na ƙoli da ɗan’adam zai iya kaiwa gare shi.

45-Suratul Jasiya

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Mafi shaharar sunanta shi ne '*Suratul Jasiya*' domin a cikinta ne wannan kalmar ta zo, watau *jasiya* a aya ta 28.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin dukkan malamai.
Ibnu Abbas (Allah ya kara masa yarda) da Katada suna ganin aya ta 14 ta sauka ne a Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta sittin da huɗu (64) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratud Dukhan*' kafin '*Suratul Ahƙaf*'.

4. Adadin ayoyinta:
Adadin ayoyinta talatin da bakwai ne (37) a lissafin mutanen Kufa, amma a lissafin mutanen Makka da Madina da Sham da Basra, adadinsu talatin da Shida ne (36).

5. Babban Jigonta:
Babban jigonta shi ne magana a kan matsalar masu bin son zuciya da bijire wa gaskiya ta hanyar tunatar da su wasu ayoyin Allah da tuna musu ranar lahira.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Ishara zuwa ga girman Alƙur'ani da mu'ujizarsa.
• Tabbatar da Kaɗaitakar Allah ta hanyar ƙarfafan dalilai da ke cikin sammai da ƙasa tare da ambaton wasu ni'imomin Allah ga bayinsa.
• Narko ga waɗanda suke yi wa Allah ƙarya suke dagewa a kan kafirci da ayyukan saɓon Allah.
• Yin tir da mushirikai masu bautar wasu ba Allah ba, bisa son zuciya da ƙaryata ranar alƙiyama da tsoratar da su asarar wannan rana da azabarta.
• Kira ga Musulmi a kan su kawar da kai daga cutarwar kafirai da yi musu alƙawarin samun nasara a kansu.
• Jan hankalin masu saɓa wa Manzo (ﷺ) da watsi da kiransa, bayan dalilai sun bayyana gare su, da yi musu kwatance da halin Banu Isra'ila waɗanda suka saɓa wa karantarwar littafinsu bayan ya zo musu.
Suratul Jasiya (1-5)
حمٓ ① تَنزِيلُ ٱلۡكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَكِيمِ ② إِنَّ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ لَأٓيَٰتٖ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ ③ وَفِي خَلۡقِكُمۡ وَمَا يَبُثُّ مِن دَآبَّةٍ ءَايَٰتٞ لِّقَوۡمٖ يُوقِنُونَ ④ وَٱخۡتِلَٰفِ ٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ وَمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مِن رِّزۡقٖ فَأَحۡيَا بِهِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَا وَتَصۡرِيفِ ٱلرِّيَٰحِ ءَايَٰتٞ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ⑤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ha Mim.

2. Saukar da Alƙur’ani daga Allah ne Mabuwayi, Mai hikima.

3. Lalle a cikin sammai da ƙasa tabbas akwai ayoyi ga muminai.

4. A cikin halittarku ma da abin da Yake bazawa na dabbobi, akwai ayoyi ga mutane masu sakankancewa.

5. Da kuma sassaɓawar dare da yini da abin da Ya saukar daga sama na arziki, sai Ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta, da kuma jujjuyawar iska, akwai ayoyi ga mutanen da suke hakalta.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe da haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori da irin waɗannan haruffa. [Dubi tafsirinmu na farkon *Suratul Baƙara* don ƙarin bayani].
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman darajar Alƙur’ani da matsayinsa babba inda ya nuna cewa, shi saukakke ne daga Allah Mabuwayi wanda babu mai iya ja da shi, mai hikima cikin halittarsa da hukuncinsa.
Sai kuma Allah ya bayyana wasu manyan dalilai na cikar Kudurarsa da ikonsa wanda duk masu imani daga bayinsa sukan iya ganin su cikin halittar sammai da ƙasa da abin da suka ƙunsa na manya-manyan halittu, kamar rana da wata da taurari a sama da duwatsu da tsirrai da koguna a ƙasa waɗanda suke nuna girman ikon Allah da cikar Kudurarsa da kyan tsarinsa.
Sai kuma ya bayyana cewa, har ila yau, akwai wasu ayoyinsa a cikin halittar su kansu mutane waɗanda ya samar da asalinsu daga taɓo sannan daga ɗigon maniyyi har suka zama cikakkun mutane. Da kuma abin da ya halitta na dabbobi masu yawo a bayan ƙasa, ya yaɗa su a ko’ina. Dukkansu ayoyi ne ga mutane masu sakankancewa da cewa Allah ne mahaliccin komai.
Hakanan game da sassaɓawar dare da yini, wannan ya zo wannan ya tafi babu ƙaƙƙautawa. Da kuma ruwa da ya saukar daga sama wanda da shi ne ya raya ƙasa bayan mutuwarta, ya fitar da tsirran cikinta da shuke-shukenta bayan a da ta bushe ƙayau babu komai a kanta.
Hakanan game da jujjuyawar iska da take kaɗawa daga nahiyoyi daban-daban, wani lokaci ta kaɗa daga arewa wani lokaci kuma daga kudu, wani lokaci ta zo da zafi wani lokaci kuma da sanyi, duka dai domin amfanin mutane da dabbobinsu da shuke-shukensu. A cikin waɗannan al’amura duka akwai ƙwararan dalilai masu nuna Kaɗaitakar Allah da cikar Kudurarsa ga mutanen da suke hankaltar ayoyin Allah, suke gane dalilan da suke ɗauke da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda hujjojin Alƙur’ani da ayoyin Allah ba su gamsar da shi ya yi imani ba, to babu abin da zai gamsar da shi har ya sa ya yi imani.

2. A koyaushe a kuma ko’ina akan iya samun wanda yake jin ana karanta masa ayoyin Allah amma ya yi ƙememe kamar bai ji komai ba, ya ci gaba da bin son zuciyarsa don girman kai da rashin tsoron Allah.

3. Yin izgili da ayoyin Allah ko masu karantar da su kafirci ne.

4. Alƙur’ani shiriya ne zuwa ga sanin Allah da siffofinsa da sunayensa da hanyoyin bauta masa, don samun yardarsa duniya da lahira. Hakanan shiriya ne zuwa ga kyawawan ayyuka da bayanin munananansu da bayanin sakamakon kowane aiki mai kyau ko mummuna.

Suratul Jasiya (6-11)

تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ نَتۡلُوهَا عَلَيۡكَ بِٱلۡحَقِّۖ فَبِأَيِّ حَدِيثِۭ بَعۡدَ ٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ يُؤۡمِنُونَ ٦ وَيۡلٞ لِّكُلِّ أَفَّاكٍ أَثِيمٖ ٧ يَسۡمَعُ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِ ثُمَّ يُصِرُّ مُسۡتَكۡبِرٗا كَأَن لَّمۡ يَسۡمَعۡهَاۖ فَبَشِّرۡهُ بِعَذَابٍ أَلِيمٖ ٨ وَإِذَا عَلِمَ مِنۡ ءَايَٰتِنَا شَيۡـٔا ٱتَّخَذَهَا هُزُوًاۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٞ مُّهِينٞ ٩ مِّن وَرَآئِهِمۡ جَهَنَّمُۖ وَلَا يُغۡنِي عَنۡهُم مَّا كَسَبُواْ شَيۡـٔا وَلَا مَا ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوۡلِيَآءَۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ١٠ هَٰذَا هُدٗىۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ لَهُمۡ عَذَابٞ مِّن رِّجۡزٍ أَلِيمٞ ١١

6. Waɗannan su ne ayoyin Allah da Muke karanta maka su da gaskiya; to da wane zance ne za su yi imani bayan (zancen) Allah da ayoyinsa?

7. Tsananin azaba ya tabbata ga duk wani maƙaryaci mai yawan saɓo.8. Yana jin ana karanta masa ayoyin Allah, sai ya doge yana mai girman kai kamar bai ji su ba; to ka yi masa albishir da azaba mai raɗaɗi.

9. Idan kuma ya san wani abu daga ayoyinmu sai ya ɗauke su abin yi wa izgili. Waɗannan suna da wata azaba mai wulaƙantarwa.

10. A gabansu akwai (wutar) Jahannama, kuma abin da suka tsuwurwurta (na dukiya da waninta), da abubuwan da suka riƙa majiɓinta ba Allah ba, (duk) ba za su amfana musu komai ba; suna kuma da (sakamakon) azaba mai girma.

11. Wannan (Alƙur'ani) shiriya ne; waɗanda kuwa suka kafirce da ayoyin Ubangijinsu, suna da (sakamakon) wata mummunar azaba mai raɗaɗi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa shi ne yake karanta masu ayoyinsa da ya saukar a cikin mafi girman littattafansa, watau Alƙur'ani, da gaskiya tare da hujjoji masu gamsarwa da za su sanya mutane su gaskata shi. To amma har idan dalilan da ke ƙunshe cikin Alƙur'ani ba su sanya mushirikai sun yi imani da shi ba, to da wane zance ne kuma za su yi imani bayan zancen Allah da ayoyinsa?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir ga duk wani babban maƙaryaci mai yawan saɓon Allah, ya kuma yi masa alƙawarin azaba mai tsanani.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana shi da cewa, shi ne wanda yakan ji ana karanta masa ayoyin Allah daga cikin Alƙur'ani amma sai ya doge a kan kafircinsa da saɓon Allah yana mai girman kai da guje wa gaskiya, kamar ba ya jin abin da ake karanta masa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya umarci Manzonsa (ﷺ) cewa ya yi masa albishir da azaba mai raɗaɗi da take jiran sa a ranar alƙiyama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara bayyana wannan taɓaɓɓen bawa nasa da cewa duk sanda wani ilimi na Alƙur'ani ya zo masa sai kawai ya shiga yi masa izgili da ba'a. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa da cewa ire-irensa masu yi wa addini da ayoyin Allah izgili a ranar alƙiyama suna da azaba ta wulaƙanci da ba su taɓa ganin irinta ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa a gabansu, watau lahira, akwai wutar Jahannama tana nan tana jiran su, kuma su daina taƙama da yawan dukiya ko wasu gumakansu da suke bauta wa a nan duniya, domin a lahira dukiyarsu da suka tara ba za ta amfane su da komai ba, hakanan allolinsu da suka riƙa bauta musu ba za su kare musu komai daga azabar Allah ba, suna da sakamakon azaba mai girma da babu wanda ya san iyakarta sai Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, wannan Alƙur'ani da ya saukar masa shiriya ne zuwa ga gaskiya, duk mai neman ya shiryu shi zai riƙe ya bi karantarwarsa sau da ƙafa. To

amma waɗanda suka kafirce wa ayoyin Ubangijinsu da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) suna da mummunar azaba mai raɗaɗi a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tafiyar jiragen ruwa a kan ruwa ɗauke da mutane da kaya masu nauyi, wata babbar aya ce da ke nuna cikar Kudurar Allah da isar ikonsa da cancantar a yi masa godiya a kan ni'imominsa.

2. Asali duk wani abu da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halitta a sama ko a ƙasa ya hore shi ne ga ɗan'adam domin ya amfana da shi matuƙar ba ya cikin da'irar abubuwan da shari'ar Allah ta haramta waɗanda su kuma ƙayyadaddu ne ba su da yawa.

3. Halittun da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi a sammai da ƙasa suna nuna kamalar Kudurarsa da faɗin mulkinsa da girmansa ne, suna kuma nuna shi ne mai aikata abin da ya ga dama babu mai iya dakatar da shi a cikin ikonsa.

4. Yin afuwa da yafiya ga azzalumi idan bai bayyana ƀarnarsa da ta'addancinsa a bayan ƙasa ba, don yin hakan ɗabi'a ce mai kyau da Allah ya umarci muminai da ita matuƙar sun hango cewa akwai maslaha a ciki.

Suratul Jasiya (12-15)
*ٱللَّهُ ٱلَّذِى سَخَّرَ لَكُمُ ٱلۡبَحۡرَ لِتَجۡرِىَ ٱلۡفُلۡكُ فِيهِ بِأَمۡرِهِۦ وَلِتَبۡتَغُواْ مِن فَضۡلِهِۦ وَلَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ١٢ وَسَخَّرَ لَكُم مَّا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعًا مِّنۡهُۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٍ لِّقَوۡمٍ يَتَفَكَّرُونَ ١٣ قُل لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ يَغۡفِرُواْ لِلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ أَيَّامَ ٱللَّهِ لِيَجۡزِىَ قَوۡمَۢا بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ١٤ مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحًا فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَنۡ أَسَآءَ فَعَلَيۡهَاۖ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ تُرۡجَعُونَ ١٥

12. Allah ne wanda Ya hore muku kogi don jiragen ruwa su riƙa gudu a cikinsa da umarninsa, don kuma ku nema daga falalarsa don kuma ku gode.

13. Ya kuma hore muku abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa gaba ɗayansu daga gare Shi. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutanen da suke yin tunani.

14. Ka ce da waɗanda suka yi imani su yi gafara ga waɗanda ba su damu da ni'imomi ko musibu na Allah ba, don Ya saka wa mutane game da irin abin da suka kasance suna aikatawa.

15. Duk wanda ya yi aiki nagari to kansa ya yi wa; wanda kuma duk ya munana to a kansa; sannan wurin Ubangijinku ne kawai za a mayar da ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falalarsa ga bayinsa da wasu ni'imomi da ya yi musu, domin su yi masa godiya a kansu, su ƀauta masa shi kaɗai ba tare da yi masa shirka ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya hore wa 'yan'adam kogi don jiragen ruwa su riƙa gudu a cikinsa da umarninsa, suna ɗauke da mutane da kayayyakinsu masu nauyi da kayansu na kasuwanci, domin su yi tafiye-tafiye na fatauci daga ƙasa zuwa wata ƙasa, don kuma su gode wa Allah wannan ni'ima da ya yi musu.
Hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hore musu duk abin da ke cikin sammai, kamar rana da wata da taurari da abin da yake ƙasa, kamar ƙoramu da bishiyoyi da duwatsu, don su zamo rahama da falala gare su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa a cikin wannan aiki nasa akwai manyan dalilai

masu tabbatar da girman Kudurarsa da Kaɗaitakarsa ga mutanen da suke tunani game da ayoyinsa, suke kuma ɗaukar izina daga gare su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya umarci muminai da su rungumi kyawawan halaye da haƙuri da yafiya ga kafirai waɗanda za su cutar da su, waɗanda kuma ba su damu da ni'imomi ko musibu na Allah ba, domin Allah ne zai saka wa bayinsa muminai masu haƙuri, zai kuma yi sakayyarsa a kan kafirai masu ta'addanci da cutar da muminai, saboda abin da suka kasance suna aikatawa a duniya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana wa kowa cewa duk wanda ya yi kyakkyawan aiki, to ya yi ne don amfanin kansa ba don Allah yana da buƙatarsa ba; wanda kuma ya yi mummunan aiki, to kansa ya cuta, ba zai cuci Allah da komai ba. Kuma dukkan halittu gaba ɗaya zuwa ga Allah ne za a mayar da su don yi musu hisabi da sakamako a kan ayyukansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi ga wannan al'umma da su guje wa bin tafarki irin na Banu Isra'ila don kada su ma su hallaka kamar yadda Banu Isra'ila suka hallaka. Saboda duk wata ni'ima da Allah ya yi wa Banu Isra'ila, to ya yi wa wannan al'umma wadda ta fi tasu, domin ya saukar musu da littafin da ya fi kowane littafi daraja da matsayi, ya kuma aiko musu da mafi ɗaukakar annabawa da manzanni duka, ya ba su shari'ar da take cike da maslahar ɗan'adam kuma dawwamammiya har abada, don haka idan suka bijire wa ni'imomin Allah, to abin da zai same su sai ya fi na Banu Isra'ila muni.

2. Idan aka samu zalunci da hassada a tsakanin wasu mutane, to dalilin rarrabuwarsu ya zo Kenan, ko da kuwa su mutane ne masu ilimi, iliminsu ba zai hana su rarrabuwa ba.

3. Riƙo da shari'ar Allah da aiki da ita shi ne kauce wa bin son zuciya, duk wanda ya bi wani abu da ya saɓa wa shari'ar Allah, to ya bi son zuciyar wasu ne.

4. Falalar Alƙur'ani da zamantowarsa littafi ne da ya ƙunshi fayyatattun dalilai masu bambance wa mutane tsakanin ƙarya da gaskiya da shiriya da ɓata, kuma shiriya da rahama ne ga mutanen da zukatansu suka cika da yaƙini.

Suratul Jasiya (16-20)
وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحُكْمَ وَٱلنُّبُوَّةَ وَرَزَقْنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَفَضَّلْنَٰهُمْ عَلَى ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٦﴾ وَءَاتَيْنَٰهُم بَيِّنَٰتٍ مِّنَ ٱلْأَمْرِ ۖ فَمَا ٱخْتَلَفُوٓا۟ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ ۚ إِنَّ رَبَّكَ يَقْضِى بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُوا۟ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿١٧﴾ ثُمَّ جَعَلْنَٰكَ عَلَىٰ شَرِيعَةٍ مِّنَ ٱلْأَمْرِ فَٱتَّبِعْهَا وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَ ٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٨﴾ إِنَّهُمْ لَن يُغْنُوا۟ عَنكَ مِنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا ۚ وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٍ ۖ وَٱللَّهُ وَلِىُّ ٱلْمُتَّقِينَ ﴿١٩﴾ هَٰذَا بَصَآئِرُ لِلنَّاسِ وَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿٢٠﴾

16. Haƙiƙa kuma Mun bai wa Banu Isra'ila littafin (Attaura) da hukunci da annabta,. Muka kuma arzuta su da tsarkakan (abubuwa), kuma Muka fifita su a kan talikai.

17. Muka kuma kawo musu (hujjoji) mabayyana na addini; to ba su sassaɓa ba, sai bayan da ilimi ya zo musu don hassada a tsakaninsu. Lalle Ubangijinka zai yi hukunci a tsakaninsu a ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna yin saɓani cikinsa.

18. Sannan Muka sanya ka a kan wata shari'a ta addini, to sai ka bi ta, kada kuma ka bi soye-soyen zukatan waɗanda ba sa sanin (gaskiya).

19. Lalle su ba za su maganta maka komai ba daga Allah. Kuma lalle azzalumai sashinsu masoya sashi ne; Allah kuwa Shi ne Majiɓincin al'amarin masu taƙawa.

20. Wannan (Alƙur'ani) izina ne ga mutane da shiriya da rahama ga mutanen da suke sakankancewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ni'imomi masu yawa da ya yi wa Banu Isra'ila, wasu ta fuskar addini wasu kuma ta fuskar rayuwarsu ta duniya. Waɗannan ni'imomi sun haɗa da:

(a) Littafin Attaura da ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya ƙunshi shiriya da hukunce-hukuncen shari'a ga Banu Isra'ila.

(b) Yin hukunci a tsakanin mutane yayin wata husuma saboda mulki yana hannunsu.

(c) Aiko annabawa masu yawa a cikinsu. Babu wata al'umma mai yawan annabawa kamar al'ummar Banu Isra'ila.

(d) Arzuta su da daɗaɗan abubuwa, don haka suka rayu cikin ni'ima da wadata.

(e) Fifita su a kan sauran mutane gaba ɗaya na zamaninsu, domin babu wata al'umma da ta haɗa mulki da annabta kamar Banu Isra'ila.

(f) Ya ba su hujjoji bayyanannu na addini waɗanda suka haɗa da mu'ujizojin da ya ba wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da kuma bayanai na wa'azi da tunatarwa da ke cikin littafin Attaura.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa ba su tashi yin saɓani a tsakaninsu ba sai bayan hujjoji sun gama tabbata a kansu ta hanyar aiko da Manzon Allah Muhammadu (ﷺ), don hassada da zalunci a tsakaninsu saboda neman shugabanci da ɗaukaka. Allah ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, zai yi hukunci a tsakaninsu ranar alƙiyama game da abin da suka kasance suna yin saɓani a kansa a nan duniya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa shi ya ɗora shi a kan wani tafarki da sunna na umarninsa irin wanda ya yi wa manzannin da suka gabace shi umarni da shi na imani da aiki nagari, ya kuma umarce shi ya bi wannan shari'ar da ya ɗora shi a kai, kada ya sake ya bi soye-soyen zukatan waɗanda ba sa sanin gaskiya ballantana su bi ta, domin bin son zuciyarsu kauce wa gaskiya ne.
Allah kuma ya nuna masa rashin amfanin bin soye-soyen zukatan masu kauce wa gaskiya da cewa, su waɗannan mutane ba za su maganta masa komai ba daga Allah, domin ba za su kare shi daga shiga wuta ba in har ya bi su kan ɓatansu, kuma su azzalumai daga kowane addini suke masoya junansu ne masu taimaka wa junansu ne wajen faɗa da muminai, to amma shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne majiɓincin al'amarin masu taƙawa da aikata umarninsa da guje wa haninsa, mai taimakon su ne koyaushe a kan abokan gabarsu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, wannan Alƙur'ani da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) hujjoji ne bayyanannu ga mutane, masu nuna musu gaskiya da ƙarya, kuma shiriya ne zuwa ga gaskiya, kuma rahama ne ga mutanen da suke sakankancewa da hujjojinsa, domin su ne masu gane tafarki madaidaici su kuma bi shi, don neman yardar Ubangijinsu da samun gidan Aljanna da kuɓuta daga wuta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muminai da kafirai ba za su taɓa zama daidai ba, domin sun sha bamban ta wajen ayyukansu, don haka dole ne su bambanta ta wajen sakamako.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci sammai da ƙasa ne don wata babbar hikima wadda ita ce bauta masa shi kaɗai, ba kamar yadda mulhidai suke gani ba.

3. Bin son zuciya abu ne mai hallakar da mai shi nan da nan ya kuma hana shi gane gaskiya.

Suratul Jasiya (21-23)

أَمْ حَسِبَ ٱلَّذِينَ ٱجْتَرَحُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن نَّجْعَلَهُمْ كَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَوَآءً مَّحْيَاهُمْ وَمَمَاتُهُمْۚ سَآءَ مَا يَحْكُمُونَ ﴿٢١﴾ وَخَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ بِٱلْحَقِّ وَلِتُجْزَىٰ كُلُّ نَفْسٍۭ بِمَا كَسَبَتْ وَهُمْ لَا يُظْلَمُونَ ﴿٢٢﴾ أَفَرَءَيْتَ مَنِ ٱتَّخَذَ إِلَٰهَهُۥ هَوَىٰهُ وَأَضَلَّهُ ٱللَّهُ عَلَىٰ عِلْمٍ وَخَتَمَ عَلَىٰ سَمْعِهِۦ وَقَلْبِهِۦ وَجَعَلَ عَلَىٰ بَصَرِهِۦ غِشَٰوَةً فَمَن يَهْدِيهِ مِنۢ بَعْدِ ٱللَّهِۚ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴿٢٣﴾

21. Yanzu waɗanda suka aikata munanan (ayyuka) suna tsammanin za Mu sanya su ne kamar waɗanda suka yi imani suka kuma yi kyawawan ayyuka, ya zamana rayuwarsu ta duniya da mutuwarsu sun zama daidai? Abin da suke hukuntawa ya munana.

22. Allah kuma Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya, don kuma a saka wa kowane rai irin abin da ya aikata, alhali kuma su ba za a zalunce su ba.

23. Shin kuwa ka ga wanda ya ɗauki son zuciyarsa (shi ne) abin bautarsa, Allah kuwa Ya ɓatar da shi a kan yana sane, Ya kuma rufe jinsa da zuciyarsa, kuma Ya sanya yana a kan ganinsa, to wane ne zai shiryar da shi in ba Allah ba? Me ya sa ba kwa wa'azantuwa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da adalcinsa da sanya bambanci tsakanin muminai masu ayyuka nagari da kuma waɗanda suka aikata munanan ayyuka, da cewa ba zai taɓa daidaita su ba a nan rayuwarsu ta duniya ko kuma a rayuwar lahira, saɓanin yadda kafirai suke tsammani cewa, su da muminai duk ɗaya ne a wurin Allah. Allah ya bayyana musu cewa, wannan wani mummunan hukunci ne suke yi, hukuncin da ba wanda zai taɓa amincewa da shi.
Sai ya bayyana musu babban dalili da ke tabbatar da adalcinsa da cewa, shi ne wanda ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya, watau domin tabbatar da gaskiya da adalci don a bauta masa shi kaɗai ba tare da an haɗa shi da komai ba, ya kuma zartar da hukuncin cewa zai yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa mai kyau ko mummuna babu wanda za a zalunta, to don haka ba zai yiwu ba ya ɗauki mutanen banza su zama ɗaya da mutanen kirki.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Annabi (ﷺ) yadda kafirai suka cuci kansu suka yi sanadiyyar da har Allah ya ɓatar da su. Ya ja hankalinsa a kan cewa ya dubi mutumin da ya mayar da bin son zuciyarsa a matsayin abin bautarsa wanda ba zai iya saɓa wa umarninsa ba, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɓatar da shi bayan ilimi ya zo masa saboda Allah ya san cewa ya cancanci ɓata, ya kuma toshe masa jinsa da zuciyarsa ta yadda, ba ya sauraron abin da zai amfane shi, ya kuma sanya rufi a kan ganinsa, ba ya ganin gaskiya ya bi ta. To irin wannan mutum wane ne zai iya dawo da shi kan hanyar gaskiya bayan Allah ya ɓatar da shi? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa mutane cewa wannan misalin ya isa ya sa su wa'azantu su gane illar bin son zuciya.

An karƀo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Abubuwa uku masu hallakarwa ne: Biye wa rowa; da biye wa son zuciya; da jiji da kai.” [Al-Bazzar, #7293. Dubi, Al-Albani, *As-Silsilatus Sahiha* #1802].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mayar da martani ga masu jingina faruwar abubuwa ga jujjuyawar zamani ko kuma daɗewa, kamar waɗanda ake kiran su *‘ad-dahriyyun’*, watau waɗanda ba su yi imani da samuwar Mahalicci ba.

2. Tabbatar da ranar alƙiyama da sakamako.

3. Zato ba ya amfanar da komai musamman a fagen aƙida.

Suratul Jasiya (24-26)

وَقَالُواْ مَا هِيَ إِلَّا حَيَاتُنَا ٱلدُّنۡيَا نَمُوتُ وَنَحۡيَا وَمَا يُهۡلِكُنَآ إِلَّا ٱلدَّهۡرُۚ وَمَا لَهُم بِذَٰلِكَ مِنۡ عِلۡمٍۖ إِنۡ هُمۡ إِلَّا يَظُنُّونَ ٢٤ وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٖ مَّا كَانَ حُجَّتَهُمۡ إِلَّآ أَن قَالُواْ ٱئۡتُواْ بِـَٔابَآئِنَآ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٢٥ قُلِ ٱللَّهُ يُحۡيِيكُمۡ ثُمَّ يُمِيتُكُمۡ ثُمَّ يَجۡمَعُكُمۡ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ لَا رَيۡبَ فِيهِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٢٦

24. Suka kuma ce: “Ai ba wata (rayuwa) sai rayuwarmu ta duniya, da za mu mutu, kuma mu rayu (watau 'ya'yansu), ba kuwa wani abu da yake hallaka mu sai juyin zamani”. Alhali kuwa ba su da wani sani game da wannan; ba abin da suke yi sai zato.

25. Idan kuma ana karanta musu ayoyinmu mabayyana, ba su da wata hujja sai kawai su ce: “Ku zo da iyayenmu idan kun kasance masu gaskiya.”

26. Ka ce: “Allah ne zai raya ku sannan ya kashe ku sannan ya tara ku a ranar alƙiyama wadda babu kokwanto game da ita, sai dai kuma yawancin mutane ba sa sanin (haka).”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani nau’i ne na kafircin mushirikai da tsananin wautarsu yayin da suke musunta tashi bayan mutuwa domin hisabi, suna cewa, wai babu wata rayuwa in ban da wannan rayuwar tasu ta duniya da suke a cikinta, sannan su mutu, sannan ‘ya’yansu su ci gaba da rayuwa a bayansu, don haka ba su yarda akwai ranar alƙiyama ba. Kuma suna ganin ma ba komai ne yake kashe su ba sai yau da gobe, watau juyawar zamani, don haka duk wata musiba idan ta same su sai su danganta ta da zamani ba tare da suna da wata hujja ta ilimi a kan da’awarsu ba sai tsantsar zato wanda ba ya amfanar da komai dangane da gaskiya.

An karƀo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah mai girma da buwaya ya ce: “Ɗan’adam yana cutar da ni, yana zagin zamani, ni kuma ni ne zamani, al’amari duka a hannuna yake, ni ne mai jujjuya dare da rana.” [Bukhari #4826 da Muslim #2246].

An karƀo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kada ɗayanku ya zagi zamani, domin Allah shi ne zamani…” [Muslim #2247].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk sanda aka karanta wa mushirikai ayoyinsa bayyanannu aka kuma ambaci tashi bayan mutuwa a cikinsu, ba su da wani abu da suke kafa hujja da shi wajen musunta tashi bayan mutuwa sai dai su riƙa cewa, wai in da gaske ne akwai ranar alƙiyama, to a

dawo musu da iyayensu da suka riga suka mutu; idan Annabi (ﷺ) da sahabbansa sun yi musu wannan, to za su yi imani da tashi bayan mutuwa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya mayar musu da martani da cewa Allah ne yake raya su shi ne kuma ya halicce su daga babu, sannan kuma shi ne zai kashe su idan ajalinsu ya zo, sannan ya sake tashin su bayan mutuwarsu ya tattara su a ranar alƙiyama wadda babu kokwanto game da zuwanta, domin yi musu hisabi da sakamako, to amma yawancinsu ba sa sanin haka. Watau ya dace a ce sun yi la'akari da halittarsu ta farko daga babu, su kafa hujja da ita a kan yiwuwar sake dawo da su bayan mutuwarsu, domin Allah da ya yi halitta da farko ba zai gagare shi ya sake dawo da abin da ya halitta ba bayan mutuwa, to amma yawancin kafirai ba sa sanin wannan don haka suke musunta ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama.

2. Tabbatar da rubuta ayyukan bayi, domin yi musu hisabi a kansu ranar alƙiyama ba tare da an zalunci wani ba.

Suratul Jasiya (27-29)
وَلِلَّهِ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَيَوْمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يَوْمَئِذٍ يَخْسَرُ ٱلْمُبْطِلُونَ ﴿٢٧﴾ وَتَرَىٰ كُلَّ أُمَّةٍ جَاثِيَةً ۚ كُلُّ أُمَّةٍ تُدْعَىٰٓ إِلَىٰ كِتَٰبِهَا ٱلْيَوْمَ تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٢٨﴾ هَٰذَا كِتَٰبُنَا يَنطِقُ عَلَيْكُم بِٱلْحَقِّ ۚ إِنَّا كُنَّا نَسْتَنسِخُ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٢٩﴾

27. Mulkin sammai da ƙasa kuma na Allah ne. Kuma ranar da alƙiyama za ta tashi, a wannan ranar mabarnata za su yi asara.

28. Za kuma ka ga kowace al'umma a durƙushe, kowace al'umma ana kiran ta zuwa ga littafinta, a wannan rana ne za a saka muku abin da kuka kasance kuna aikatawa.

29. (Za a ce da su): "Wannan Littafinmu ne da yake yi muku furuci da gaskiya. Lalle Mu mun kasance Muna rubuta abin da kuka kasance kuna aikatawa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mulkin sammai da ƙasa nasa ne shi kaɗai, shi ne mai sarrafa su yadda ya ga dama, don haka shi kaɗai ya cancanta a bauta masa, yana da kuma isasshen iko na ya tashi matattu a ranar alƙiyama don yi wa kowa hisabi da sakamako a kan aikinsa, to a ranar ne mabarnata waɗanda suka bauta wa wasu ba Allah ba suka ƙaryata ranar alƙiyama za su yi babbar asara.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, a wannan ranar zai ga kowace al'umma a durƙushe a kan gwiwoyinsu suna sauraron yadda za a yi da su, kowace al'umma za a kira ta zuwa ga littafin ayyukanta wanda mala'iku suka rubuta a nan duniya, kowa a yi masa sakamako gwargwadon aikinsa mai kyau ko mummuna. Sannan za a tabbatar musu cewa, ba a zalunce su ba game da hukuncin da aka yanke musu, domin littafin da mala'iku suka rubuta na ayyukansu yana ba da shaida ne a kansu da tsantsar gaskiya, domin Allah ne da kansa ya umarci waɗannan mala'ikun su riƙa rubuta ayyukan mutane a duniya don yanke musu hanzari a lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani da ayyuka na ƙwarai su ne dalilan shiga Aljanna ranar alƙiyama.

2. Imani yana tare da kyawawan ayyuka koyaushe, domin da su ne yake haɓaka ya ƙaru.

3. Babu rabon da ya kai samun shiga gidan Aljanna.4. Girman kai da sabawa da aikata miyagun laifuffuka, su ne suka hana kafirai yin imani da ayoyin Allah da ake karanta musu.

Suratul Jasiya (30-31)
فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَيُدۡخِلُهُمۡ رَبُّهُمۡ فِي رَحۡمَتِهِۦۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡمُبِينُ ٣٠ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ أَفَلَمۡ تَكُنۡ ءَايَٰتِي تُتۡلَىٰ عَلَيۡكُمۡ فَٱسۡتَكۡبَرۡتُمۡ وَكُنتُمۡ قَوۡمٗا مُّجۡرِمِينَ ٣١

30. To amma waɗanda suka yi imani suka yi ayyuka nagari, to Ubangijinsu zai shigar da su cikin rahamarsa. Wannan shi ne rabo mabayyani.31. Amma kuma waɗanda suka kafirce (za a ce da su): “Yanzu ashe ayoyina ba su kasance ana karanta muku su ba, sai kuka yi girman kai, kuka kasance mutane masu manyan laifuka?”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda mutane za su kasu gida biyu a lahira bayan yi musu hisabi. Kaso na farko, su ne waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa suka kuma yi kyawawan ayyuka, to waɗannan Allah zai shigar da su gidan Aljanna da rahamarsa, wannan sakamako kuma da ya ba su shi ne rabo mabayyani da babu kamarsa.
Kaso na biyu kuwa, su ne waɗanda suka kafirce wa Allah da manzanninsa, to su waɗannan za a tambaye su cikin zargi da tuhuma cewa, shin manzanni ba su zo suna karanta musu ayoyin Allah ba? To amma maimakon su miƙa wuya su yi imani sai suka ɗaura rawanin girman kai suka bijire wa imani da ayoyin Allah, don haka suka zama mutane masu manyan laifuka da suka haɗa da kafirci da shirka da saɓon Allah iri-iri?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mushirikai suna ƙaryata ranar alƙiyama ba su yarda za ta zo ba; to idan ma an matsa musu da bayaninta don nuna musu su daina kokwanto game da ita sai su riƙa izgili suna nuna cewa a zuciyarsu akwai zato mai rauni game da alƙiyama amma fa ba su da tabbas a kai.

2. Duk munanan ayyukan da kafirai suka aikata a nan duniya sai sun bayyana a fili a gare su ranar alƙiyama don su gane dacewar sakamakon da aka yi musu a kansu.

3. Yin izgili da ayoyin Allah kafirci ne.

4. Idan duniya da ƙyale-ƙyalenta sun ruɗi mutum sai ta hana shi tunani game da ranar lahira, ta shagaltar da shi daga yin kyakkyawan tanadi domin lahira.

5. Kafirai za su dawwama a cikin wuta ba za su taɓa fita ba har abada.

6. Dukkan wasu kalmomi na yabo da kirari a sammai da ƙasa Allah ne ya fi cancantar su, domin shi ne mahaliccin sammai da ƙasa da duk sauran halittu baki ɗaya.

Suratul Jasiya (32-37)
وَإِذَا قِيلَ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ وَٱلسَّاعَةُ لَا رَيۡبَ فِيهَا قُلۡتُم مَّا نَدۡرِي مَا ٱلسَّاعَةُ إِن نَّظُنُّ إِلَّا ظَنّٗا وَمَا نَحۡنُ بِمُسۡتَيۡقِنِينَ ٣٢ وَبَدَا لَهُمۡ سَيِّـَٔاتُ مَا عَمِلُواْ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٣٣ وَقِيلَ ٱلۡيَوۡمَ نَنسَىٰكُمۡ كَمَا نَسِيتُمۡ لِقَآءَ يَوۡمِكُمۡ هَٰذَا وَمَأۡوَىٰكُمُ ٱلنَّارُ وَمَا لَكُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٣٤

ذَٰلِكُم بِأَنَّكُمُ ٱتَّخَذْتُمْ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ هُزُوًا وَغَرَّتْكُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا ۚ فَٱلْيَوْمَ لَا يُخْرَجُونَ مِنْهَا وَلَا هُمْ يُسْتَعْتَبُونَ ﴿٣٥﴾ فَلِلَّهِ ٱلْحَمْدُ رَبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَرَبِّ ٱلْأَرْضِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٣٦﴾ وَلَهُ ٱلْكِبْرِيَآءُ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٣٧﴾

32. Idan kuma aka ce, lalle alƙawarin Allah gaskiya ne, alƙiyama kuma babu kokwanto a game da ita kukan ce: “Mu ba mu da sanin mece ce ma alƙiyama, mu ba abin da muke tsammani (game da ita) sai zato, mu kuma ba mu da tabbas.”

33. Kuma irin munanan ayyukan da suka aikata suka bayyana a gare su, kuma abin da suka kasance suna yi wa izgili ya saukar musu.

34. Aka kuma ce: “A yau za Mu manta da ku kamar yadda kuka manta haɗuwarku da wannan rana taku, makomarku kuma wuta ce, kuma ba ku da wasu mataimako.

35. “Wannan kuwa saboda lalle kun ɗauki ayoyin Allah abin yi wa izgili, rayuwar duniya kuma ta ruɗe ku.” To a yau ba za a fitar da su daga cikinta ba, kuma su ba za a nemi su kawo hanzarinsu ba.

36. To yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin sammai kuma Ubangijin ƙasa, Ubangijin talikai.

37. Girma nasa ne a cikin sammai da ƙasa, kuma Shi ne Mabuwayi, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai suka riƙa ƙaryata ranar alƙiyama duk kuwa da hujjojin da ake karanta musu, masu nuna gaskiyar Manzon Allah (ﷺ) da gaskiyar abin da ya zo musu da shi. Idan aka faɗa musu cewa, lalle alƙawarin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu na tayar da su don yi musu hisabi gaskiya ne, kuma ranar alƙiyama gaskiya ce babu kokwanto a game da ita, sai su kada baki su ce, su ba su san da wata ranar alƙiyama ba; ba abin da suke ji game da ita in ban da zato mai rauni wai ana cewa za ta zo, amma su fa ba su da wani tabbas a kan haka.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, ranar alƙiyama za ta zo, a ranar munanan ayyukan kafirci da saɓon Allah da suka aikata a duniya zai bayyana a gare su, sannan kuma azabar da suke yi wa izgili idan ana tsoratar da su da ita ta auka musu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, a ranar zai bar su ne a cikin wuta ya yi watsi da su sakamakon manta wannan ranar da suka yi, don haka suka ƙi yi mata wani tanadi na imani da aiki nagari. Sai ya tabbatar musu da cewa, makomarsu ita ce wutar Jahannama, kuma ba su da wasu mataimaka da za su kuɓutar da su daga azabar Allah.
Allah kuma ya tabbatar musu mummunan aikin da suka yi har ya kai su ga wannan mummunan hali na azaba da wulaƙanci, watau shi ne izgilin da suka riƙa yi da ayoyin Allah da kuma ruɗar su da rayuwar duniya ta yi da ƙyale-ƙyalenta da sha’awe-sha’awenta, don haka suka rungume ta suka manta da Allah. To a ranar za a tabbatar musu cewa ba za a fitar da su daga cikin wannan azabar ba; za su yi ta zama ne a cikinta har abada, sannan kuma ba za a mayar da su duniya ba domin su gyara ayyukansu, don kuwa Allah ba zai taɓa yarda da su ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kammala Surar da kalmomin yabo da godiya gare shi Ubangijin sammai da ƙasa, Ubangijin dukkan halittu. Ya tabbatar wa da kansa girma da cikar iko a sammai da ƙasa, shi ne kuma Mabuwayi wanda babu mai iya ja da shi ko ya fi ƙarfinsa, mai hikima kuma a cikin halittarsa da shari’arsa da ayyukansu duka.m

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayani a kan girman Alƙur'ani da babban matsayinsa don bayin Allah su haskaka da haskensa su yi riƙo da shiriyarsa.

2. Babbar manufar halittar sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, don su zama ƙaƙƙarfar hujja da ke nuna Ɗayantakar Allah da kuma cancantar a bauta masa shi kaɗai, don kuma bayi su yi kyakkyawan tanadi na zuwan ranar alƙiyama da abin da ta ƙunsa na hisabi da sakamako.

3. Kafirai sun bijire wa tuntuntuni game da halittar sammai da ƙasa, waɗanda suke nuna Kaɗaitakar Allah da cikar Kudurarsa.

4. Dukkan abin da aka bauta wa ba Allah ba to kasasshe ne bai cancanci bauta ba. Allah ne kaɗai ya cancanci bauta domin shi ne mahaliccin sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu.

5. Babu wani bayani ɗaya da za a samu daga wani manzo daga cikin manzannin Allah da yake nuna a bauta wa wani ba Allah ba. Duk annabawan Allah sun yi kira ne zuwa ga kaɗaita Allah da bauta da guje wa shirka.

6. Amsa addu'a tana daga cikin fitattun dalilai masu nuna samuwar Allah da cancantar a bauta masa shi kaɗai.

7. Duk waɗanda suka bauta wa wasu ba Allah ba, to a ranar alƙiyama sai sun yi baram-baram da su su nesanta kawunansu daga bautarsu.

\

46-Suratul Ahƙaf

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna '*Suratul Ahƙaf*'. Hakanan aka ji wannan suna daga wasu sahabbai, kamar Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) da Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya kara masa yarda).

An kuma kira ta da wannan suna saboda lafazin *Al-Ahƙaf* bai zo a wata sura ba sai a cikinta. *Al-Ahƙaf* sunan wani gari ne a ƙasar Yaman inda Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka rayu.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin dukkan malamai, kamar yadda Kurɗubi ya ambata a tafsirinsa. Amma wasu malamai sun keɓe wasu ayoyi huɗu waɗanda suka ce sun sauka ne bayan hijira, watau *Madaniyya* ne, su ne aya ta 10 da aya ta 15 zuwa ta 18 da kuma aya ta 35.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta sittin da biyar (65) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratul Jasiya*' kafin '*Suratuz Zariyat*'.

4. Adadin ayoyinta:
Ayoyinta talatin da biyar ne (35) a lissafin mutanen Kufa, amma a lissafin malaman sauran garuruwa ayoyinta talatin da huɗu ne (34).

5. Babban Jigonta:
Surar tana magana ne a kan tabbatar da Kaɗaitakar Allah da manzancin Annabi (ﷺ) da kuma tabbatar da tashi bayan mutuwa domin yin hisabi da sakamako.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin matsayin Alƙur'ani da mu'ujizarsa.
• Tabbatar da Kaɗaitakar Allah ta hanyar kafa hujja da halittar sammai da ƙasa da kuma tabbatar da sakamakon ayyuka a ranar lahira.
• Rushe bautar duk wani abin bauta ba Allah ba da nuna rashin cancantar a bauta masa ko a sanya shi abokin tarayya da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Rushe da'awar cewa Alƙur'ani maganar wani ne ba Allah ba.
• Tabbatar da manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ) da kafa shaida a kan haka da mai shaida daga Banu Isra'ila.
• Yabon waɗanda suka yi imani da Alƙur'ani da ambaton wasu kyawawan siffofinsu tare da tsokaci a kan wasu halaye na kafirai, kamar hassada wadda ta sanya su ƙaryata Annabi (ﷺ).

• Labarin wata mu’ujiza ta Manzon Allah (ﷺ), watau zuwan aljannu wurinsa da sauraron karatunsa na Alƙur’ani da yin imani da shi.
• A cikinta an kawo maganar kyautata wa iyaye da kyakkyawar addu’a gare su da kuma ‘ya’ya.

Suratul Ahƙaf (1-6)
حمٓ ۝١ تَنزِيلُ ٱلۡكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَكِيمِ ۝٢ مَا خَلَقۡنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَأَجَلٖ مُّسَمّٗىۚ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ عَمَّآ أُنذِرُواْ مُعۡرِضُونَ ۝٣ قُلۡ أَرَءَيۡتُم مَّا تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَرُونِي مَاذَا خَلَقُواْ مِنَ ٱلۡأَرۡضِ أَمۡ لَهُمۡ شِرۡكٞ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِۖ ٱئۡتُونِي بِكِتَٰبٖ مِّن قَبۡلِ هَٰذَآ أَوۡ أَثَٰرَةٖ مِّنۡ عِلۡمٍ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ۝٤ وَمَنۡ أَضَلُّ مِمَّن يَدۡعُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَن لَّا يَسۡتَجِيبُ لَهُۥٓ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَهُمۡ عَن دُعَآئِهِمۡ غَٰفِلُونَ ۝٥ وَإِذَا حُشِرَ ٱلنَّاسُ كَانُواْ لَهُمۡ أَعۡدَآءٗ وَكَانُواْ بِعِبَادَتِهِمۡ كَٰفِرِينَ ۝٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ha Mim.

2. Saukar da Alƙur’ani daga Allah ne Mabuwayi, Mai hikima.

3. Ba Mu halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu ba sai don gaskiya da kuma (zuwa) wani lokaci ƙayyadajje. Waɗanda kuwa suka kafirta masu bijire wa abin da aka yi musu gargaɗi da shi ne.

4. Ka ce: “Shin kun ga abin da kuke bauta wa ba Allah ba, ku nuna min abin da suka halitta na ƙasa, ko kuwa suna da tarayya ne a (halittar) sammai; ku kawo mini wani littafi da yake gabanin wannan (Alƙur’anin), ko kuma wani ɓirɓishi na ilimi idan kun kasance masu gaskiya.”

5. Wane ne ya fi ɓata fiye da wanda yake bauta wa wani ba Allah ba, wanda ba zai amsa masa ba har zuwa ranar alƙiyama, kuma su (ababen bautar) rafkanannu ne game da bautar da suke yi musu?

6. Idan kuma aka tashi mutane (ababen bautar) za su kasance abokan gabarsu, kuma su zamo masu musanta bautar tasu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da wasu haruffa kamar yadda ya buɗe wasu surori da suka gabace ta da irin waɗannan haruffa. [Dubi tafsirinmu na farkon *Suratul Baƙara* domin ƙarin bayani].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi wannan Alƙur’ani da cewa, saukakke ne daga wajen Allah Mabuwayi wanda babu mai iya rinjayar sa, mai hikima a cikin halittarsa da shari’arsa da tsarinsa.
Sai kuma ya bayyana cewa, bai halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu don wasa ba, ya halicce su ne don gaskiya da wata babbar hikima wadda ta ƙunshi nuna wa bayinsa girman Kudurarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da yi masa shirka ba, sannan kuma mutane su rayu a bayan ƙasa da kyakkyawar zamantakewa da khilafa har zuwa wani ƙayyadajjen lokaci da Allah ne kaɗai ya san shi. To amma duk da wannan kafirai ba su daina bijire wa abin da ake musu gargaɗi da shi ba a cikin littafin Allah suna watsi da shi suna bin son zuciyarsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya tambayi mushirkai masu bauta wa gumaka ba Allah ba su faɗa masa, wane abu ne suka halitta a bayan ƙasa, shin sun halicci wani dutse ne ko kuma sun halicci wata ƙorama? Ko kuma sun yi tarayya da Allah ne wajen halittar sammai don haka suna da wani kaso a ciki? Ya neme su da su zo masa da wani littafi da Allah ya saukar musu kafin Alƙur’ani ko wani ɓurɓushin ilimi na mutanen farko da ke nuna cewa gumakan da suke bauta wa sun cancanci a

bauta musu. Babu shakka ba za su sami wannan ba, saboda haka suna jayayya ne kawai ba da wata hujja ba ta ilimi ko ta hankali.
Sannan Allah ya bayyana wautarsu a fili yayin da suke bauta wa gunki wanda ba zai taba amsa addu'ar ɗayansu ba har alƙiyama ta tashi, hasali ma su waɗannan gumakan da suke bauta wa ba su ma san suna yi ba ballantana har su amsa musu addu'o'insu, ko su amfanar da su ko su kare musu wata cuta. Don haka babu ɓatacce kamar mai bautar wani ba Allah ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana rashin amfanin bautar wani ba Allah ba a ranar alƙiyama, lokacin da za a tattara su gaba ɗayansu domin yi musu hisabi, to a lokacin ababen bautarsu ba Allah ba za su zame musu abokan gaba, su riƙa nesanta kansu da su, har su nuna musu cewa, su ba su san da bautar da suka yi musu ba a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin ƙin gaskiya ta mushirikai wadda har ta kai su su kira ayoyin Alƙur'ani da cewa sihiri ne, tare da cewa sun san babban bambanci tsakanin sihiri da abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi na gaskiya. Sun san cewa sihiri ba ya fitowa sai daga mugun mutum mai mugun hali, Annabi Muhammadu kuwa sun san nagartarsa sarai.

2. Taimakon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga Annabi (ﷺ) da goyon bayansa da ya nuna masa babbar shaida ce a kan gaskiyar abin da ya zo da shi na wahayi, ba shi ne ya ƙage shi ba, domin da ya yi wa Allah ƙarya, to da bai ƙyale shi hakanan ba, da lalle ya saukar masa da azabarsa wadda babu wani wanda zai iya kare shi a nan duniya.

3. Annabi (ﷺ) bai san gaibu ba sai abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ga dama ya sanar da shi.

4. Samuwar dalilan da suke tabbatar da gaskiyar manzancin Annabi (ﷺ) a littattafan da suka gabata.

Suratul Ahƙaf (7-9)
وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ قَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِلْحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمْ هَٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ ۝٧ أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰهُ ۖ قُلْ إِنِ ٱفْتَرَيْتُهُۥ فَلَا تَمْلِكُونَ
لِى مِنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا ۖ هُوَ أَعْلَمُ بِمَا تُفِيضُونَ فِيهِ ۦ كَفَىٰ بِهِۦ شَهِيدًۢا بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۖ وَهُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ۝٨ قُلْ مَا كُنتُ بِدْعًا مِّنَ ٱلرُّسُلِ وَمَآ أَدْرِى
مَا يُفْعَلُ بِى وَلَا بِكُمْ ۖ إِنْ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَىَّ وَمَآ أَنَا۠ إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ ۝٩

7. Idan kuma an karanta musu ayoyinmu bayyanannu sai waɗanda suka kafirce wa gaskiya lokacin da ta zo musu su ce: "Wannan sihiri ne mabayyani."

8. A'a, cewa dai suka yi: "Kagar sa ya yi." Ka ce: "Idan har na ƙage shi ne to ba za ku amfana min komai ba game da Allah; Shi ne Ya fi sanin abin da kuke kutsawa cikinsa; Shi Ya isa Mai shaida tsakanina da ku; kuma Shi ne Mai gafara, Mai rahama."

9. Ka ce: "Ba ni ne farau ba daga manzanni, kuma ba ni da sanin abin da za a yi min da abin da za a yi muku; ni ba abin da nake bi sai abin da ake yiwo min wahayinsa, kuma ni ba wani ba ne face mai gargaɗi mai bayyanawa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin taurin kan kafirai a yayin da ake karanta musu ayoyin Allah bayyanannu masu tabbatar da Kaɗaitakarsa sai su ƙaryata su, har su zargi Manzon Allah da cewa, sihiri ne ƙarara ya zo musu da shi, ba wahayi ne daga Allah ba.

Haka kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kafirai wani lokaci suna zargin Annabi (ﷺ) cewa shi ne ya ƙagi Alƙur'ani ya danganta shi da Allah, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya faɗa musu cewa, idan har shi ne ya ƙagi Alƙur'ani ya danganta wa Allah, to ai su ba wata kariya da za su iya ba shi idan Allah ya yi nufin yi masa azaba, don haka me zai sa ya jefa kansa cikin haɗari yana sane? Sannan ya tabbatar musu da cewa Allah ne mafi sanin irin kutsen da suke yi wajen sukan littafinsa Alƙur'ani da sukan Manzonsa (ﷺ) kuma ya isa ya zama shaida tsakaninsa da su ya kuma bayyana wane ne mai gaskiya shi ko su. To amma idan sun gane sun tuba sun yi imani, to Allah mai gafarta zunuban bayinsa ne mai rahama ne gare su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya sake tabbatar wa mushirikai masu ƙaryata shi suna zarginsa da yi wa Allah ƙarya, cewa ba fa shi ne farau ba da Allah ya aiko da manzanci ballantana har su riƙa mamakin zamantowarsa manzon Allah; manzanin Allah masu yawa sun gabace shi, to don me suke musun manzancinsa. Sannan ya shaida musu cewa shi ba masanin gaibu ba ne don bai san abin da Allah zai yi masa ba ko ya yi musu a nan duniya, shi kawai abin da aka yi masa wahayi yake bi, don haka yana magana yana kuma aiki ne da wahayin da aka yi masa, shi ba wani ne ba sai mai gargaɗi mai bayyana gargaɗinsa ga kowa.

An karɓo daga Ummul Ala, (Allah ya ƙara mata yarda), ta ce: Lokacin da Usmanu ɗan Maz'un (Allah ya ƙara masa yarda) ya rasu sai na ce: "Rahamar Allah ta tabbata a gare ka ya Baban Sa'ib, shaidata a gare ka ita ce, lalle Allah ya karrama ka." Sai Annabi (ﷺ) ya ce mata: "Mene ne ya sanar da ke cewa Allah ya karrama shi?" Sai ta ce: "Ban sani ba, mahaifina da mahaifiyata fansa ne gare ka ya Ma'aikin Allah." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Amma Usmanu lalle wallahi mutuwa ta zo masa, kuma lalle ni ina yi masa fatan alheri. Wallahi ban sani ba, alhali ni Manzo ne na Allah, me za a yi masa." Sai ta ce: "To na rantse da Allah ba zan sake tsarkake wani ba bayansa har abada, kuma hakan ya baƙanta mini." Sai ta ce: Sai na yi barci sai aka nuna mini wani idon ruwa mai gudana na Usman, sai na zo wurin Manzon Allah na ba shi labari sai ya ce: "Wannan aikinsa ne." [Bukhari #2687].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Samun dalilai da suke tabbatar da annabcin Annabi (ﷺ) a cikin littattafan annabawan da suka gabata.

2. Girman kai game da karɓar gaskiya bayan gane ta zalunci ne.

3. Wanda ya jahilci abu yakan nuna ƙiyayya gare shi ko ma ya ƙaryata shi.

4. Jiji da kan mushirkai da ruɗuwarsu da addininsu shi ya sa suka riƙa zaton cewa babu wani alheri a cikin Musulunci, domin da akwai wani abin alheri a cikinsa to da raunanan mutane da fakiransu ba za su riga su karɓar sa ba, domin su ne suka fi cancantar karɓar duk wani abu mai daraja da ɗaukaka.

5. Daga cikin manya-manyan manufofin Alƙur'ani akwai isar da gargaɗi ga azzalumai da kuma albishir ga muminai.

Suratul Ahƙaf (10-14)
قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن كَانَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ وَكَفَرْتُم بِهِۦ وَشَهِدَ شَاهِدٌ مِّنْ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ عَلَىٰ مِثْلِهِۦ فَـَٔامَنَ وَٱسْتَكْبَرْتُمْ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٠﴾
وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَوْ كَانَ خَيْرًا مَّا سَبَقُونَآ إِلَيْهِ ۚ وَإِذْ لَمْ يَهْتَدُوا۟ بِهِۦ فَسَيَقُولُونَ هَٰذَآ إِفْكٌ قَدِيمٌ ﴿١١﴾ وَمِن قَبْلِهِۦ كِتَٰبُ مُوسَىٰٓ

إِمَامًا وَرَحۡمَةٗۚ وَهَٰذَا كِتَٰبٞ مُّصَدِّقٞ لِّسَانًا عَرَبِيّٗا لِّيُنذِرَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ وَبُشۡرَىٰ لِلۡمُحۡسِنِينَ ١٢ إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُواْ رَبُّنَا ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسۡتَقَٰمُواْ فَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ١٣ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِ خَٰلِدِينَ فِيهَا جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٤

10. Ka ce: “Ku ba ni labari, idan (Alƙur’ani) ya kasance daga wurin Allah yake, kuka kuma kafirce masa, kuma wani mai shaida daga Banu Isra’ila ya ba da shaida a kan irinsa, sai ya yi imani (da shi) ku kuma kuka yi girman kai; to lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai.”

11. Waɗanda kuma suka kafirce suka ce wa waɗanda suka yi imani: “Da (addinin) ya kasance alheri ne, da su ba su riga mu zuwa gare shi ba.” To tunda kuwa ba su shiriya da shi ba, to za su riƙa cewa: “Wannan ƙarya ce daɗaɗɗiya.”

12. A gabaninsa kuwa akwai littafin Musa wanda yake jagora ne da rahama. Wannan littafin kuma mai gaskata (na gabaninsa) ne a harshen Larabci, don ya gargaɗi waɗanda suka kafirta da kuma yin albishir ga masu kyautatawa.

13. Lalle waɗanda suka ce: “Allah ne Ubangijinmu”, sannan suka tsaya kyam, to babu wani tsoro a gare su, kuma su ba za su yi baƙin ciki ba.

14. Waɗannan su ne ‘yan Aljanna madawwama a cikinta don sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana wa mushirikai gaskiyar Alƙur’ani wanda suke ƙaryatawa, ya umarci Manzonsa (ﷺ) cewa ya tambaye su, me za su ce idan Alƙur’ani ya tabbata daga Allah yake, kuma aka samu wani mai shaida daga Banu Isra’ila ya ba da shaida a kan ingancinsa, duba da abin da ya zo na bayaninsa a cikin littafin Attaura, sannan ya yi imani da shi, su kuma mushirkai suka kafirce masa, girman kai ya hana su su yi imani bayan gaskiya ta bayyana a fili. Yanzu in suka yi haka ba su tabbata azzalumai ba? To lalle su sani Allah ba ya shiryar da mutane azzalumai masu ƙin gaskiya saboda girman kai da son zuciya.

An karɓo daga Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Ban ji Manzon Allah (ﷺ) yana faɗa wa wani mai tafiya a bayan ƙasa cewa shi ɗan aljanna ne ba, sai ga Abdullahi ɗan Salam. A kansa ne wannan ayar ta sauka, watau: (…kuma wani mai shaida daga Banu Isra’ila ya ba da shaida a kan irinsa)". [Bukhari#3812 da Muslim#2483].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata wautar ta mushirikai da rashin hankalinsu lokacin da suka riƙa yi wa muminai izgili suna faɗa musu cewa, wai da a ce abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi gaskiya ne akwai kuma alheri a cikinsa, to da waɗannan bayin talakawan ba za su riga su karɓar sa ba, domin suna ganin waɗanda suka yi imani da Manzon Allah (ﷺ) ba manyan mutane ba ne, wasu faƙirai ne, wasu bayi, wasu raunanan mutane, su kuwa ba su cancanci samun wata ɗaukaka ko girma ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu martani da cewa, tun da taurin kansu ya fito fili ba su karɓi shiriyarsu ba, to za su riƙa sukan abin da Manzo ya zo musu da shi cewa wata daɗaɗɗiyar ƙarya ce su kuma ba za su riƙe ƙarya ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da ingancin Alƙur’ani da gaskiyarsa ya nuna musu cewa, kafin a saukar da Alƙur’ani a can baya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Musa Attaura wadda ba sa tababa a kanta, wadda ya sanya ta jagora a kan gaskiya kuma rahama ga wanda ya yi imani da ita ya bi karantarwarta. Shi kuma wannan Alƙur’anin da aka saukar wa Manzon Allah (ﷺ) littafi ne

wanda yake gaskata littattafan da suka gabace shi, kuma Allah ya saukar da shi da harshen Larabci don ya gargaɗi mutanen da suka zalunci kawunansu da aikata shirka da saɓon Allah, kuma har ila yau bushara ne ga masu kyautata alaƙarsu da mahaliccinsu da alaƙarsu da sauran halittunsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana bayinsa nagari da kyakkyawan sakamakonsu, da cewa lalle sun yi imani cewa Allah ne Ubangijinsu, ba su da wani ubangiji ba shi ba, sannan suka daidaita a kan imani da aiki na ƙwarai, to waɗannan babu wani tsoro tare da su game da abin da za su fuskanta a lahira, kuma ba za su yi baƙin ciki a kan abin da suka bari ba a duniya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, waɗannan su ne ‘yan Aljanna masu shigar ta su dawwama a cikinta har abada, sakamakon kyawawan ayyukan da suka yi a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman matsayin iyaye da wajabcin yi musu biyayya a kan duk abin da babu saɓon Allah a cikinsa, da kyautata musu, musamman ma mahaifiya wadda ta sha fama da wahalhalun ɗanta, tun daga samun cikinsa take ta fama ba cikakkiyar lafiya, babu isasshen barci har ta zo wahalar haihuwarsa, daga nan ta shiga ɗawainiyar shayar da shi har zuwa lokacin da ya isa yaye, sannan ta ci gaba da kula da shi da yi masa tarbiyya har ya kai munzalin cikakken mutum da zai iya kula da kansa.

2. Nuni zuwa ga mafi ƙarancin lokacin ciki, watau wata shida.

An karɓo daga Abul Aswad Ad-Du’ali ya ce: An kawo wata mata gaban Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ta haihu a cikin wata shida, sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya yi niyyar ya sa a jefe ta, sai ‘yar’uwarta ta sami Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) ta ce masa: “Umar yana niyyar ya sa a jefe mini ‘yar’uwata, ina roƙon ka don Allah idan ka san tana da wani hanzari to ka faɗa mini.” Sai Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Lalle tana da hanzari.” Sai ta yi kabbara da ƙarfi har sai da Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya jiyo kabbararta. Sai ta je ta sami Umar ta faɗa masa cewa Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce ‘yar’uwata tana da hanzari. Sai Umar ya aika a kirawo masa Aliyyu, ya tambaye shi mene ne hanzarinta? Sai ya ce: Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: “Kuma iyaye mata za su shayar da ‘ya’yansu tsawon shekara biyu cikakku…” [*Al-Baƙara*: 233] Ya kuma ce: “…ɗaukan cikinsa da yaye shi kuma wata talatin ne…” Don haka ɗaukan cikinsa wata shida ne, sauran wata ashirin da huɗu kuma na yaye ne. Sai Umar ya ƙyale ta. Sannan kuma ta sake haihuwar wani yaron a cikin wata shida.” [Abdurrazaƙ, *Al-Musannaf* #13444].

An ruwaito irin wannan ruwayar daga Abdullahi ɗan Abbas tare da Sayyidina Usman (Allah ya ƙara masa yarda). [Dubi, Abdurrazaƙ, Al-*Musannaf* #13446 da 13447].

3. Shekara arba’in lokaci ne na cikar ƙarfi da hankali na mutum, shi ya sa ake aiko annabawa a waɗannan shekarun.

4. An keɓance shekara arba’in da ambato a nan, saboda shi ne lokacin da nauyi yakan yi yawa a kan mutum, domin ya yi aure ya fara hayayyafa, don haka kullum yana cikin ɗawainiyar nemo wa iyalansa abinci. Ita ma mace a lokacin ɗawainiyar kula da gidanta da ‘ya’yanta sun fara yi mata nauyi, to akwai yiwuwar duk wannan ya shagaltar da su su manta da kula da iyayensu da kyautata musu yayin da tsufa ya riga ya kama su, don haka ya dace a tunatar da su haƙƙoƙin iyayensu da kyautata musu.

5. Addu’ar uba ga ɗansa ana sa ran karɓuwarta.

6. Yin tawassali da tuba zuwa ga Allah, domin yana daga cikin kyawawan ayyukan mutum.

7. Kyautata wa iyaye da yi musu addu’a da yi wa ‘ya’ya addu’a yana daga cikin mafi kyan ayyuka.

8. Nuni zuwa ga cewa irin wannan addu’a ita ce ake sa ran karɓuwarta a wurin Allah, domin shi ne da kansa ya koyar da ita.

Suratul Aḥkaf (15-16)

وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ إِحْسَٰنًا ۖ حَمَلَتْهُ أُمُّهُۥ كُرْهًا وَوَضَعَتْهُ كُرْهًا ۖ وَحَمْلُهُۥ وَفِصَٰلُهُۥ ثَلَٰثُونَ شَهْرًا ۚ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَبَلَغَ أَرْبَعِينَ سَنَةً قَالَ رَبِّ أَوْزِعْنِىٓ أَنْ أَشْكُرَ نِعْمَتَكَ ٱلَّتِىٓ أَنْعَمْتَ عَلَىَّ وَعَلَىٰ وَٰلِدَىَّ وَأَنْ أَعْمَلَ صَٰلِحًا تَرْضَىٰهُ وَأَصْلِحْ لِى فِى ذُرِّيَّتِىٓ ۖ إِنِّى تُبْتُ إِلَيْكَ وَإِنِّى مِنَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿١٥﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ نَتَقَبَّلُ عَنْهُمْ أَحْسَنَ مَا عَمِلُوا۟ وَنَتَجَاوَزُ عَن سَيِّـَٔاتِهِمْ فِىٓ أَصْحَٰبِ ٱلْجَنَّةِ ۖ وَعْدَ ٱلصِّدْقِ ٱلَّذِى كَانُوا۟ يُوعَدُونَ ﴿١٦﴾

15. Kuma Mun yi wa mutum wasiyya da kyautata wa mahaifansa; mahaifiyarsa ta ɗauki cikinsa a wahalce, ta kuma haife shi a wahalce; ɗaukan cikinsa da yaye shi kuma wata talatin ne, har lokacin da ya cika ƙarfinsa ya kai shekara arba’in ya ce: “Ya Ubangijina, Ka kimsa min yadda zan gode wa ni’imarka, wadda Ka ni’imta ni da ita da kuma mahaifana, kuma (Ka ba ni iko) in yi aiki nagari wanda za Ka yarda da shi, kuma Ka kyautata min zurriyata; lalle ni na tuba a gare Ka, kuma lalle ni ina daga cikin Musulmi.”

16. Waɗannan su ne waɗanda Muke karɓar mafi kyan abin da suka aikata, kuma Muke yafe musu munanan ayyukansu, suna cikin ‘yan Aljanna; (wannan) alƙawari ne na gaskiya wanda suka kasance ana yi musu alƙawarinsa (a duniya).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa mutum wasiyya da ya kyautata wa iyayensa a lokacin rayuwarsu da bayan mutuwarsu, ta hanyar da ba ta saɓa wa shari’a ba, musamman ma mahaifiyarsa wadda ta yi wahalhalun ɗaukan cikinsa da haihuwarsa. Ta yi ɗawainiyar ɗaukan cikinsa da yaye shi cikin wata talatin. Har lokacin da ya kai cikar ƙarfinsa, hankalinsa ya cika bayan ya kai shekara arba’in, to a lokacin zai riƙa addu’a yana roƙon Allah ya kimsa masa godiya a kan ni’imar da ya yi masa, ya kuma yi wa iyayensa, ya kuma hore masa yin aiki na ƙwarai da ya yarda da shi, ya kuma karɓi aikin nasa. Sannan ya roƙi Allah ya gyara masa ‘ya’yansa da ya ba shi, su zama na ƙwarai masu biyayya. Sannan ya tuba zuwa ga Allah a kan zunubbansa da ya aikata, ya tabbatar da cewa, shi yana cikin Musulmi masu miƙa wuya ga umarnin Allah masu bin sa sau da ƙafa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana girman sakamakon mutane masu irin wannan hali, da cewa yana karɓar mafi kyan ƙwararan ayyukansu yana kuma yafe musu laifukansu domin suna cikin ‘yan Aljanna. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, wannan alƙawari ne na gaskiya da ya yi musu sai ya tabbata babu makawa domin shi ba ya saɓa alƙawarinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babban abin da iyaye za su kira ɗansu zuwa gare shi shi ne, abin da zai rabauta da shi duniya da lahira rabo na har abada.

2. Mutane da aljannu duka ɗaya ne wajen tafka asara ga wanda ya aikata kafirci da saɓon Allah.

3. Nuni zuwa ga cewa su ma aljannu suna mutuwa tsareku bayan tsareku.

4. Mutane mataki-mataki ne wajen sakamakonsu gwargwadon ayyukansu masu kyau ko munana.

5. Haɗarin faɗaɗawa wajen more jin daɗi na duniya, domin zai iya shagaltar da bawa game da lahira.

6. Ana gaggauto wa kafirai jin daɗinsu tun a nan duniya domin su rasa komai a lahira.

7. Tsananin narko ga masu girman kai da ayyukan fasiƙanci.

Suratul Ahƙaf (17-20)

وَٱلَّذِى قَالَ لِوَٰلِدَيۡهِ أُفٍّ لَّكُمَآ أَتَعِدَانِنِىٓ أَنۡ أُخۡرَجَ وَقَدۡ خَلَتِ ٱلۡقُرُونُ مِن قَبۡلِى وَهُمَا يَسۡتَغِيثَانِ ٱللَّهَ وَيۡلَكَ ءَامِنۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقٌّ فَيَقُولُ مَا هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٧ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ حَقَّ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقَوۡلُ فِىٓ أُمَمٖ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِم مِّنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ خَٰسِرِينَ ١٨ وَلِكُلّٖ دَرَجَٰتٞ مِّمَّا عَمِلُواْۖ وَلِيُوَفِّيَهُمۡ أَعۡمَٰلَهُمۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ١٩ وَيَوۡمَ يُعۡرَضُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ عَلَى ٱلنَّارِ أَذۡهَبۡتُمۡ طَيِّبَٰتِكُمۡ فِى حَيَاتِكُمُ ٱلدُّنۡيَا وَٱسۡتَمۡتَعۡتُم بِهَا فَٱلۡيَوۡمَ تُجۡزَوۡنَ عَذَابَ ٱلۡهُونِ بِمَا كُنتُمۡ تَسۡتَكۡبِرُونَ فِى ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَبِمَا كُنتُمۡ تَفۡسُقُونَ ٢٠

17. Wanda kuma ya ce da mahaifansa: “Tir da ku, yanzu kwa riƙa yi min alƙawarin za a fito da ni (daga ƙabarina), alhali kuwa tuni wasu al’ummu sun shuɗe gabanina?” Su kuma suna ta roƙon Allah da cewa: “Kaiconka, ka yi imani mana, lalle alƙawarin Allah tabbatacce ne,” sannan ya ce: “Wannan ba wani abu ba ne face tatsuniyoyin mutanen farko!”

18. Waɗannan su ne waɗanda kalmar azaba ta tabbata a kansu cikin al’ummun da suka gabace su na aljannu da mutane; lalle su sun kasance asararru.

19. Kuma kowane yana da darajoji (na sakamakon) abin da suka aikata; don kuma tabbas zai cika musu sakamakon ayyukansu, ba kuma za a zalunce su ba.

20. (Ka tuna) kuma ranar da za a bijiro da waɗanda suka kafirta a gaban wuta, (a ce da su): “Kun tafiyar da jin daɗinku a rayuwarku ta duniya, kuma kun more ta, to a yau za a saka muku da azabar wulaƙanci saboda kun kasance kuna girman kai a bayan ƙasa ba da wata hujja ba, saboda kuma kun kasance kuna yin fasiƙanci.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana misalin wanda yake kangare wa iyayensa, yake ƙuntata musu, har ta kai ya dubi fuskarsu ya yi tir da su wai don suna yi masa wa’azi; suna kiran sa ya yi imani da Allah da ranar lahira, shi kuma yana ƙaryata su saboda sun faɗa masa cewa, za a tashe shi daga ƙabarinsa da ransa don yi masa hisabi a kan miyagun ayyukansa. Shi kuma yana nuna musu cewa, wannan maganar ba gaskiya ba ce, saboda ai wai a baya can mutane da yawa sun mutu ba a taɓa tashin ɗaya daga cikinsu da ransa ba. Su kuma iyayensa suna ta roƙon Allah ya shiryi ɗansu ya yi imani, suna gargaɗin sa cewa, lalle ya yi imani idan kuwa ba haka ba, to hallaka za ta tabbata a kansa, domin alƙawarin Allah na tashi bayan mutuwa gaskiya ne babu kokwanto a cikinsa. Shi kuma yana ƙara fanɗarewa yana gaya musu cewa, wannan magana da suke faɗa masa ba komai ba ce face tatsuniyoyin mutanen farko ba gaskiya ne ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, irin waɗannan mutane su ne waɗanda azabar Allah ta riga ta tabbata a kansu cikin jerin al’ummun da suka gabata na aljannu da mutane cewa dukkansu hasararru ne ‘yan wuta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin cewa, duka ɓangarorin nan biyu na ‘yan Aljanna da ‘yan wuta kowanne yana da matakai daban-daban na sakamakon abin da suka aikata, ‘yan Aljanna suna da matakai na can ƙoli, ‘yan wuta kuwa suna da matakai na can ƙasan ƙasa, Allah kuma zai cika musu sakamakon ayyukansu ba tare da an zalunce su ba a ranar alƙiyama, ta hanyar rage wa wani kyakkyawan aikinsa, ko ƙara wa wani mummunan aikin da bai aikata ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa kafirai halin tashin hankali da za su fuskanta a ranar alƙiyama lokacin da za a bijirar da su a gaban wuta don yi musu azaba a cikin izgili da cusa musu baƙin ciki, za a riƙa faɗa musu cewa, ai sun gama more jin daɗinsu a rayuwarsu ta duniya sun sha sharholiyarsu yadda suke so, to amma fa a yau za su ɗandani azabar da za ta ƙaskantar da su ta wulaƙantar da su saboda girman kai da suka nuna a bayan ƙasa suka ƙi karɓar gaskiya da kuma ficewa daga yi wa Allah biyayya ta hanyar aikata kafirci da saɓon Allah.

An karɓo daga Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na shiga wurin Manzon Allah (ﷺ) a lokacin da ya ƙaurace wa matansa sai na gan shi kwance a kan tabarma babu wata shimfiɗa a kanta har kabar tabarmar ta yi burɗun-burɗun a gefen jikinsa, yana kishingiɗe a kan wani matashin kai na fatar da aka cika ta da zaren itaciyar dabino, sai na yi masa sallama… Umar ya ci gaba da cewa: Sai na ɗaga kaina na dubi ko'ina a cikin gidan Manzon Allah (ﷺ) ban ga wani abu da zai ja hankalina ba sai wasu buzaye guda uku da ke saƙale. Sai na ce: "Ka roƙi Allah ya yalwata wa al'ummarka, domin an yalwata wa Farisawa da Rumawa, an ba su duniya ga shi kuma su ba ma sa bauta wa Allah." Annabi (ﷺ) yana kishingiɗe, da jin wannan magana sai ya tashi zaune ya ce: "Yanzu kana cikin kokwanto ne ya ɗan Khaɗɗab? Waɗancan fa mutane ne da aka gaggauto musu da jin daɗinsu a rayuwarsu ta nan duniya." [Bukhari #2468 da Muslim #479].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Da'awar annabawa a dunƙule, ita ce kira zuwa ga bautar Allah shi kaɗai da watsi da shirka.

2. Manzannin Allah ba su san gaibu ba sai abin da Allah ya ga dama ya sanar da su.

3. Baki shi ke yanka wuya. Adawa sun roƙi Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gaggauto musu da azaba idan har ya kasance mai gaskiya, sai abin da suka roƙa da bakinsu ya sauko musu, watau azabar Allah.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hore wa Adawa ƙarfi fiye da na kafiran Kuraishawa, to amma duk da wannan sai da ya hallaka su yayin da suka zaɓi kafirci suka yi girman kai.

5. Lallashin zuciyar Manzon Allah (ﷺ) da ba shi labarin Adawa da irin abin da suka yi wa Annabinsu Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga ƙarshe Allah ya taimake shi a kansu.

Suratul Aḥƙaf (21-26)

*وَٱذۡكُرۡ أَخَا عَادٍ إِذۡ أَنذَرَ قَوۡمَهُۥ بِٱلۡأَحۡقَافِ وَقَدۡ خَلَتِ ٱلنُّذُرُ مِنۢ بَيۡنِ يَدَيۡهِ وَمِنۡ خَلۡفِهِۦٓ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّا ٱللَّهَ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ٢١ قَالُوٓاْ أَجِئۡتَنَا لِتَأۡفِكَنَا عَنۡ ءَالِهَتِنَا فَأۡتِنَا بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٢٢ قَالَ إِنَّمَا ٱلۡعِلۡمُ عِندَ ٱللَّهِ وَأُبَلِّغُكُم مَّآ أُرۡسِلۡتُ بِهِۦ وَلَٰكِنِّيٓ أَرَىٰكُمۡ قَوۡمٗا تَجۡهَلُونَ ٢٣ فَلَمَّا رَأَوۡهُ عَارِضٗا مُّسۡتَقۡبِلَ أَوۡدِيَتِهِمۡ قَالُواْ هَٰذَا عَارِضٞ مُّمۡطِرُنَاۚ بَلۡ هُوَ مَا ٱسۡتَعۡجَلۡتُم بِهِۦۖ رِيحٞ فِيهَا عَذَابٌ أَلِيمٞ ٢٤ تُدَمِّرُ كُلَّ شَيۡءِۭ بِأَمۡرِ رَبِّهَا فَأَصۡبَحُواْ لَا يُرَىٰٓ إِلَّا مَسَٰكِنُهُمۡۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٢٥ وَلَقَدۡ مَكَّنَّٰهُمۡ فِيمَآ إِن مَّكَّنَّٰكُمۡ فِيهِ وَجَعَلۡنَا لَهُمۡ سَمۡعٗا وَأَبۡصَٰرٗا وَأَفۡـِٔدَةٗ فَمَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُمۡ سَمۡعُهُمۡ وَلَآ أَبۡصَٰرُهُمۡ وَلَآ أَفۡـِٔدَتُهُم مِّن شَيۡءٍ إِذۡ كَانُواْ يَجۡحَدُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٢٦

21. Ka kuma tuna ɗan'uwan Adawa (watau Hudu) lokacin da ya gargaɗi mutanensa a *al-Ahƙafu*, alhali haƙiƙa masu gargaɗi sun shuɗe a gabaninsa da kuma a bayansa (suna cewa:) "Kada ku bauta wa (kowa) sai Allah, lalle ni ina jiye muku tsoron azabar wani yini mai girma."

22. Sai suka ce: "Yanzu ka zo ne don ka kawar da mu daga ababen bautarmu? To ka zo mana da abin da kake yi mana alƙawarin narko (da shi) idan ka kasance cikin masu gaskiya."

23. Sai ya ce: "Lalle sani yana wurin Allah kawai, ni kuma ina isar muku abin da aka aiko ni da shi ne, sai dai kuma ni ina ganin ku mutane ne masu wauta."

24. To lokacin da suka gan ta (azabar) wani hadari ne mai gindayawa, ya doso wa kwarurukansu sai suka ce: "Wannan hadari ne mai ba mu ruwa!" A'a, (ba ku sani ba) shi ne abin da kuke neman gaggautowarsa, watau iska da take cike da azaba mai raɗaɗi.

25. Tana ruguza kowane irin abu da umarnin Ubangijinta, sai suka wayi gari ba abin da ake gani sai (kufaifan) gidajensu. Kamar haka Muke saka wa mutane masu manyan laifuka.

26. Haƙiƙa Mun kafa su (a bayan ƙasa) kafawar da ba Mu yi muku irinta ba, Muka kuma sanya musu ji da gani da tunani, sai jin nasu da ganinsu da tunaninsu ba su amfana musu komai ba, tunda sun kasance suna musanta ayoyin Allah, abin da kuma suka kasance suna yi wa izgili ya auka musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin Annabinsa Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda yake da dangantaka ta jini da ƙabilar Adawa mazauna wani yanki da ake ce wa *al-Ahƙaf* a can kudancin tsibirin Larabawa a ƙasar Yaman, lokacin da ya gargaɗe su da su ji tsoron aukuwar azabar Allah a kansu, kuma ba shi ne farau ba wajen irin wannan gargaɗin, gabaninsa annabawan Allah sun shuɗe, wasu kuma sun zo a bayansa, dukkansu kuma sun riƙa sanar da mutanensu cewa, kada su bauta wa kowa sai Allah kaɗai. Don haka Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna wa mutanensa cewa yana jiye musu tsoron azabar wannan yini mai girma, watau ranar alƙiyama.
To amma bayan sun ji wannan nasiha ta Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sai suka mayar masa da martani da zargin sa cewa ya zo ne kawai don ya raba su da bautar allolinsu, su kuma ba za su taɓa yarda da haka ba, don haka suna kiran sa da ya kawo musu azabar da yake tsorata su da ita idan har ya kasance mai gaskiya ne cikin abin da yake da'awa.
Sai Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nuna musu cewa, abin ba a hannunsa yake ba, bai kuma san takamaiman lokacin da azabar za ta auka musu ba, Allah ne kaɗai ya san wannan, shi kawai manzo ne da yake isar musu da saƙon da aka aiko shi da shi, to amma kuma ya lura cewa su mutane ne masu cike da wauta, ba su san abin da zai amfane su ba ballantana su karɓe shi ko abin da zai cutar da su don su guje shi.
To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da azabarsa, watau wata iska mai tsananin ƙarfi, yayin da suka hango hadari ya lulluɓe samaniya ya doshi kwaruruwansu, sai suka fara murna suna cewa, lalle ga hadari nan zai yi musu ruwa, sai Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana musu cewa ba hadari ne ba; wannan wata iska ce mai ɗauke da azaba mai raɗaɗi, kuma tana ruguza kowane abu da ta biyo ta kansa daga cikin abubuwan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce ta ta ruguza. Sai suka wayi gari ta ruguza komai ba abin da ta bari, ta hallaka dabbobinsu da dukiyoyinsu da su ma kansu, ba abin da ake gani sai kufan gidajensu da suke zaune a cikinsu don su zama shaidar cewa a da an taɓa yin wasu mutane a wurin. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, kamar yadda ya yi musu irin wannan mummunan sakamako saboda kafircinsu da ƙaryata Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), to hakanan zai saka wa duk wasu mutane masu manyan laifuka irin nasu, matuƙar ba su tuba sun koma ga Allah ba.

An karɓo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Annabi (ﷺ) ya kasance idan ya ga hadari ko iska ta taso sai a ga alamar tashin hankali a fuskarsa, sai ta ce: Ya Manzon Allah, mutane idan sun ga hadari sukan nuna farin cikinsu don suna tsammanin za su sami ruwan sama, amma kai kuwa idan ka ga hadari ya taso sai a ga fuskarka ta canza? Sai yace: “Ya A’isha, mene ne zai amintar da ni cewa, ba wata azaba ce a cikinsa ba, alhali an taɓa yi wa wasu mutane azaba da iska, wasu kuma da suka ga azabar sai suka riƙa cewa: 'Wannan hadari ne mai mana ruwa'.” [Bukhari #4829]

An karɓo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Annabi (ﷺ) ya kasance idan iska ta taso yana cewa: “Ya Allah ina roƙon ka alherinta da alherin da yake cikinta da alherin da aka aiko ta da shi. Ina kuma neman tsarinka daga sharrinta da sharrin abin da yake cikinta da sharrin da aka aiko ta da shi.” Idan kuma hadari ya haɗo sai kamanninsa su canja, ya kasa zaune ya kasa tsaye, amma da zarar ruwa ya sauka sai hankalinsa ya kwanta. Sai na tambaye shi game da haka, sai ya ce: “Ban sani ba ko abin ya zama kamar yadda Adawa ne suka riƙa cewa: ‘Wannan hadari ne mai ba mu ruwa.’” [Muslim #899]

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin ƙarfin da ya ba wa Adawa don ya zama izina ga mutanen Makka, inda ya nuna musu cewa, lalle ya kafa Adawa a bayan ƙasa, ya kuma ƙarfafe su da abin da bai ƙarfafi mutanen Makka da shi ba, na ni’imomin duniya da ƙarfin halitta da dukiya mai tarin yawa, amma duk suka butulce wa wannan ni’imar da ya yi musu, sai azabarsa ta saukar musu ya hallaka su baki ɗaya, domin kuma ya ba su ji da gani da tunani, to amma duk sun yi watsi da su, ba su tsaya sun yi sauraro na fahimta ba, ba su kalli ayoyin Allah sun wa’azantu da su ba, ba su kuma yi tunani da hankulan da ya ba su ba, sai ba su tsinana musu komai ba lokacin da azabar Allah ta sauko musu saboda sun kasance suna kafirce wa ayoyin Allah suna yi wa Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) izgili idan ya tsoratar da su azabar Allah, sai ga shi abin da suka kasance suna yi wa izgili ya sauka a kansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mai hankali shi ne wanda ya wa’azantu da waninsa, jahili wawa kuwa shi ne wanda ya zama wa’azi ga waninsa.

2. Yi wa kafiran Kuraishawa kashedi da wa’azi ta hanyar nuna musu cewa, allolin da suke bauta wa ba Allah ba ba za su amfane su da komai ba, domin da suna da amfani to da sun amfani al’ummun da suka gabata yayin da azabar Allah ta zo musu.

Suratul Ahƙaf (27-28)
وَلَقَدۡ أَهۡلَكۡنَا مَا حَوۡلَكُم مِّنَ ٱلۡقُرَىٰ وَصَرَّفۡنَا ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٢٧ فَلَوۡلَا نَصَرَهُمُ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ قُرۡبَانًا ءَالِهَةَۖ بَلۡ ضَلُّواْ عَنۡهُمۡۚ وَذَٰلِكَ إِفۡكُهُمۡ وَمَا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ ٢٨

27. Haƙiƙa mun hallakar da abin da yake kewaye da ku na (mutanen) alƙaryu, Mun kuma jujjuya musu ayoyi (ta fuskoki daban-daban) don su dawo (kan hanya).

28. To me ya hana allolin da suka riƙe suna bautar su ba Allah ba, su taimake su? A’a, sun dai ɓace musu ne. Wannan kuma da man ƙaryarsu ce da kuma abin da suka kasance suna ƙagawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tunatar da mutanen Makka azabar da ya yi wa wasu al’ummu masu maƙotaka da su waɗanda suka kafirce wa ayoyinsa, kamar Adawa da Samudawa da

mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanen Madyana. Duk waɗannan al'ummu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu ayoyi daban-daban domin su wa'azantu su dawo kan tafarki madaidaici, amma suka bijire, sai ya hallaka su gaba ɗaya.
Sannan kuma su mushirikan Kuraishawa sun san dai cewa, waɗancan al'ummu sun yi ƙaurin suna wajen bautar gumaka da mayar da su alloli ba Allah ba, to shin me ya hana su taimaka musu su kare su daga azabar Allah lokacin da ta zo musu? Sam ba su kawo musu wani ɗauki ba, a maimakon haka sai ma suka neme su suka rasa su, to da man ai ƙarya ce kawai suka riƙe wadda su ne suka ƙaga wa kawunansu ita don haka ba su yi musu wani amfani ba, ashe wannan ya ishi mushirikai wa'azi da izina.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin kyakkyawan ladabin sauraron karatu, yin shiru da kawaici don samun natsuwar fahimtar abin da ake karantawa.

2. A cikin aljannu akwai masu wa'azi da suke yi wa 'yan'uwansu gargaɗi, suna kiran su zuwa ga imani da kaɗaita Allah.

3. Saƙon Annabi Muhammadu (ﷺ) ya haɗa har da aljannu, don haka su ma dole ne su yi imani da shi don su sami kuɓuta daga azabar Allah.

4. Cikin aljannu akwai masana waɗanda suke da ilimin abin da littattafan annabawan baya suka ƙunsa na Tauhidi da manzanci.

5. Za a azabta aljannun da suka bijire wa gaskiya suka bar tafarki madaidaici.

6. Imani da cewa aljannu da mutane duka ɗaya suke wajen sakamako mai kyau da mummuna.

7. Kunyata mushirikan Makka da ganin bekensu ta hanyar nuna musu cewa, ga aljannu waɗanda ba jinsinsu ɗaya da Manzon Allah ba kuma ba harshensu ɗaya ba, sun saurari karatun Alƙur'ani sun kuma fahimci gaskiyar da ya ƙunsa har sun yi imani da shi sun koma suna kiran 'yan'uwansu zuwa gare shi. To amma su mushirikai sun kafirce wa Manzon Allah wanda suke jinsi ɗaya da shi, yana kuma karanta musu littafin da aka saukar da shi cikin harshensu na Larabci. Lalle wannan abin takaici ne game da su.

8. Bayanin mu'ujizar Annabi (ﷺ).

Suratul Ahƙaf (29-32)
وَإِذۡ صَرَفۡنَآ إِلَيۡكَ نَفَرٗا مِّنَ ٱلۡجِنِّ يَسۡتَمِعُونَ ٱلۡقُرۡءَانَ فَلَمَّا حَضَرُوهُ قَالُوٓاْ أَنصِتُواْۖ فَلَمَّا قُضِيَ وَلَّوۡاْ إِلَىٰ قَوۡمِهِم مُّنذِرِينَ ٢٩ قَالُواْ يَٰقَوۡمَنَآ إِنَّا سَمِعۡنَا كِتَٰبًا أُنزِلَ مِنۢ بَعۡدِ مُوسَىٰ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِ يَهۡدِيٓ إِلَى ٱلۡحَقِّ وَإِلَىٰ طَرِيقٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٣٠ يَٰقَوۡمَنَآ أَجِيبُواْ دَاعِيَ ٱللَّهِ وَءَامِنُواْ بِهِۦ يَغۡفِرۡ لَكُم مِّن ذُنُوبِكُمۡ وَيُجِرۡكُم مِّنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ ٣١ وَمَن لَّا يُجِبۡ دَاعِيَ ٱللَّهِ فَلَيۡسَ بِمُعۡجِزٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَيۡسَ لَهُۥ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءُۚ أُوْلَٰٓئِكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ٣٢

29. (Ka tuna) kuma lokacin da Muka juyo maka da wata jama'a ta aljannu don su saurari Alƙur'ani. To lokacin da suka halarto shi, sai suka ce: "Ku yi shiru;" sannan lokacin da aka gama (karatunsa) sai suka juya zuwa mutanensu suna yi musu gargaɗi.

30. Suka ce: “Ya ku mutanenmu, haƙiƙa mu mun jiwo wani littafi da aka saukar bayan Musa, mai gaskata abin da yake gabaninsa, yana shiryarwa zuwa gaskiya da kuma zuwa tafarki madaidaici.

31. “Ya ku mutanenmu, ku amsa wa mai kira (zuwa ga) Allah, kuma ku yi imani da shi, (Allah) zai gafarta muku zunubanku ya kuma tsare ku daga azaba mai raɗaɗi.

32. “Duk wanda kuwa bai amsa wa mai kira (zuwa ga) Allah ba, to ba zai gagara ba a bayan ƙasa, kuma ba shi da wasu mataimaka in ba shi ba. Waɗannan suna cikin ɓata mabayyani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kamar yadda a cikin mutane akwai waɗanda suka yi imani akwai kuma waɗanda suka ƙafirce, to hakanan su ma aljannu a cikinsu akwai waɗanda suka ba da gaskiya da Annabi (ﷺ), akwai kuma waɗanda ba su ba da gaskiya ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da Manzonsa (ﷺ) lokacin da ya juyo masa wata jama’a ta aljannu suka halarci majalisinsa inda yake karanta Alƙur’ani, suka saurari karatunsa cikin natsuwa, har wasu daga cikinsu suna umartar wasu da su yi shiru don su sami jin abin da yake karantawa sosai. Lokacin da suka gama sauraro, sai suka yi imani da shi, suka kuma juya suka koma cikin jama’arsu ta aljannu suna yi musu gargaɗi da wa’azi a kan su yi imani da Allah da Manzonsa da Alƙur’anin da aka saukar masa.

An karɓo daga Alƙamatu almajirin Abdullahi ɗan Mas’ud ya ce: Na tambayi ɗan Mas’ud cewa, shin Annabi (ﷺ) ya tafi da ɗaya daga cikinsu a daren da ya haɗu da aljannu? Sai ya ce: “Bai tafi da kowa daga cikinmu ba, sai dai wata rana mun neme shi mun rasa shi, sai muka riƙa cewa, an yi masa kisan gilla ko kuma an ɗauke shi, ba mu san me yake ciki ba. Muka kwana cikin matuƙar bakin ciki da tashin hankali. Asuba tana kawo kai sai muka gan shi yana dawowa ta nahiyar dutsen Hira, sai muka ba shi labarin halin da muka shiga, sai ya ce mana: “Mai kira ne daga cikin aljannu ya zo ya kirawo ni, sai na je musu na karanta musu Alƙur’ani.” Sai ya tafi da mu ya nuna mana guraben zamansu da ɓirɓishin wutacensu.” [Muslim #450]

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Na kwana ina karanta wa aljannu Alƙur’ani waɗanda suka taru a wani wuri mai suna *Al-Hajun*.” [Ahmad #3954 da Ibn Hibban #6319]

Al-Hajun sunan wuri ne a farkon Mina. Wasu sun ce maƙabartar mutanen Makka ce, tana kallon gidan Abu Musa Al-Ash’ari. [Dubi, Al-Bakri, *Mu’ujamu Mas-tu’ujim*, juzu’i na 2, shafi na 428]

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin da jama’ar aljannun nan suka koma wajen jama’arsu sai suka gaya musu cewa, lalle sun saurari karatun wani littafi da Allah ya saukar da shi bayan Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), wanda yake gaskata abin da littattafan Allah na baya suka zo da shi, yana kuma shiryarwa zuwa ga gaskiya da tafarki madaidaici, watau Musulunci.
Sai kuma suka kira jama’arsu cewa lalle su amsa kiran Annabi (ﷺ) da yake yi musu zuwa ga gaskiya, su yi imani da cewa, shi Manzon Allah ne wanda ya aiko zuwa gare su, idan sun yi imani Allah zai gafarta musu zunubansu, kuma ya tserar da su daga azaba mai raɗaɗi wadda take jiran duk wani wanda ya ƙi yin imani. Sannan suka ja musu kunne suka yi musu kashedi da cewa, duk wanda bai bi Annabi Muhammadu a kan gaskiyarsa da yake kira zuwa gare ta ba, to ba zai gagari Allah a bayan ƙasa ba ballantana ya tsere masa, kuma ba shi da wasu masoya ba Allah ba waɗanda za su kuɓutar da shi daga azabar Allah idan ya damƙe shi. Waɗanda za su zaɓi saɓa wa Manzo (ﷺ) to waɗannan suna cikin ɓata mabayyani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daga cikin manyan dalilan yiwuwar tashi bayan mutuwa akwai halittar sammai da ƙasa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi.

2. Haƙuri babban hali ne na manzannin Allah. Annabi (ﷺ) ya samu kaso mafi tsoka na siffar haƙuri da juriya game da ƙiyayyar da mushirikai suka nuna masa, ya tsaya kai da fata ya jajirce a kan bayyana gaskiya ga al'ummarsa, tsananin gabar kafirai da taron danginsu a kansa bai sa shi ya ja da baya ba ko ya sassauta da'awarsa har lokacin da Allah ya ba shi nasara a kansu, ya kafa daular Musulunci ta farko wadda ta yi ta faɗaɗa har Musulunci ya shiga ko'ina da ina a duniya. Allah ya ƙara tsira da salati a gare shi.

3. Alƙur'ani littafi ne da ya ƙunshi wa'azi da gargaɗi ga mutum da aljan duka.

4. Daga cikin adalcin Allah da rahamarsa ga bayinsa ba zai azabtar da wani ba sai wanda ya bijire wa ɗa'arsa, ya ƙi aiki da umarninsa da haninsa.

Suratul Ahƙaf (33-35)

أَوَ لَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّ ٱللَّهَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَلَمۡ يَعۡيَ بِخَلۡقِهِنَّ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يُحۡۦِيَ ٱلۡمَوۡتَىٰۚ بَلَىٰٓۚ إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٣٣ وَيَوۡمَ يُعۡرَضُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ عَلَى ٱلنَّارِ أَلَيۡسَ هَٰذَا بِٱلۡحَقِّۖ قَالُواْ بَلَىٰ وَرَبِّنَاۚ قَالَ فَذُوقُواْ ٱلۡعَذَابَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡفُرُونَ ٣٤ فَٱصۡبِرۡ كَمَا صَبَرَ أُوْلُواْ ٱلۡعَزۡمِ مِنَ ٱلرُّسُلِ وَلَا تَسۡتَعۡجِل لَّهُمۡۚ كَأَنَّهُمۡ يَوۡمَ يَرَوۡنَ مَا يُوعَدُونَ لَمۡ يَلۡبَثُوٓاْ إِلَّا سَاعَةٗ مِّن نَّهَارِۭ بَلَٰغٞۚ فَهَلۡ يُهۡلَكُ إِلَّا ٱلۡقَوۡمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٣٥

33. Ba sa ganin cewa Allah wanda Ya halicci sammai da ƙasa, Bai kuma gajiya ba wajen halittar su, Mai iko ne kan Ya raya matattu? Haka ne, lalle Shi Mai iko ne a kan komai.

34. Kuma a ranar da za a bijiro da waɗanda suka kafirta a gaban wuta (a ce da su): "Yanzu wannan ba gaskiya ba ne?" Suka ce: "Haka ne (gaskiya ne) Mun rantse da Ubangijinmu." Sai Ya ce: "To ku ɗanɗani azaba saboda abin da kuka kasance kuna yi na kafirci."

35. To ka yi haƙuri kamar yadda masu azama daga manzanni suka yi haƙuri, kada kuma ka nemi gaggauto musu (azaba). Kai ka ce ranar da za su ga abin da ake yi musu alƙawarinsa kamar ba su zauna (a duniya) ba sai wani ɗan lokaci na wuni. (Wannan) isar da saƙo ne. To akwai waɗanda za a halakar in ba mutane fasiƙai ba?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa kafirai masu ƙaryata tashin alƙiyama cewa, su tsaya su yi tunani su ga cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda ya halicci sammai da ƙasa bai kuma gajiya ba wajen halittar su duk kuwa da girmansu da faɗinsu, babu shakka zai iya raya halittu bayan mutuwarsu, ya tashe su domin yi musu hisabi da sakamako domin shi mai iko ne a kan komai babu abin da yake gagarar sa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tsoratar da kafirai azabar ranar alƙiyama da suke ƙaryatawa da cewa ranar da za a bijiro su a kan wuta, a cikin zargi da wulaƙanci a riƙa tambayar su cewa, yanzu wannan azabar da suke gani a sarari har yanzu ba gaskiya ba ce, kamar yadda suke faɗa a duniya? A nan kuma dole su amsa su tabbatar da cewa, lalle gaskiya ne, sai mala'iku cikin izgili su ce musu, to su ɗanɗani azaba saboda kafircinsu da suka riƙa yi a duniya, watau wannan ne sakamakonsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi zuciyar Manzonsa (ﷺ) game da abin da yake gani na wulaƙanci da tsangwama daga kafirai, ya umarce shi ya yi haƙuri ya jure kamar yadda manyan manzannin Allah masu azama suka yi, watau Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Ibrahim

(Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Ya kuma neme shi da kada ya gaggauto musu da azabar da suke ta neman sa da ya kawo musu ita saboda jahilcinsu da tsananin wautarsu. Ba su san da cewa duk wani abu mai zuwa to a kusa yake? Don haka duk ranar da abin da ake yi musu alƙawari na azaba ya zo musu za su ga kamar dai ba su zauna a duniya ba sai ɗan wani lokaci na wuni, saboda tsawon azabar da za su tsinci kansu a cikinta.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, wannan Alƙur'ani da ya saukar masa saƙo ne wanda ya ishi mutane har da aljannu, domin yana ƙunshe da duk bayanin da suke buƙatar sa na rayuwarsu ta duniya da ta lahira. Sannan ya bayyana masa cewa ba wanda za a hallaka da azaba sai fasiƙan mutane waɗanda suka rungumi kafirci da saɓon Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin manyan ayyukan kafirai bayan sun kafirce wa Allah, sai su hana wa kansu bin duk wata hanyar Allah, su kuma hana wasu bin ta. Wannan aiki ne na shugabannin kafirci a ƙowane zamani a kuma kowane wuri.

2. Yana daga cikin hana bin hanyar Allah da kafiran Kuraishawa suka yi, ciyar da mutane abinci a ranar yaƙin Badar don su ba su ƙarfin gwiwar tsayawa su yaƙi Manzon Allah (ﷺ) da Musulmi. Da kuma hana mutane sauraron karatun Alƙur'ani.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ɓata kyawawan ayyukan kafirai da suke yi don samun lada, kamar ciyar da mabuƙata da taimakon raunana da sada zumunci. Allah ba zai ba su lada a kansu ba saboda kafircinsu. Hakanan yana lalata ayyukansu na ƙulle-ƙullen makirci don rusa Musulunci da Musulmi, ba kuma zai ba su nasara ba, kamar yadda ya faru a lokacin yaƙin Badar, inda suka kashe maƙudan kuɗaɗe don tattara mutane da ɗaukar ɗawainiyarsu don su yaƙi Musulmi, amma daga ƙarshe aka karya su, Musulmi suka yi nasara a kansu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana gyara al'amuran duk waɗanda suka yi imani da shi da abin da ya aiko Manzonsa da shi na Alƙur'ani da sunna, suka yi aiki da karantarwarsa, suka kiyaye dokokinsa, to rayuwarsu da al'amuransu na duniya za su yi kyau, hakanan al'amuransu na lahira su ma za su yi kyau.



47-Suratu Muhammad

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ta shahara da sunan '*Suratu Muhammad*' domin sunan Annabi (ﷺ) da ya zo a cikin ayarta ta 2. A nan ne kuma aka fara ambaton wannan suna kafin na cikin '*Suratu Ali-Imrana*'.
Hakanan ana kiran ta da sunan '*Suratul Kital*' domin lafazin *Al-Kital,* watau 'yaƙi' ya zo a cikin aya ta 20. Sannan a cikinta an zaburar da Musulmi a kan yaƙar kafirai.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya* a wurin dukkan malamai, kamar yadda Ibn Aɗiyya ya ambata. Amma aya ta 13 ta sauka ne bayan Annabi (ﷺ) ya fito daga garin Makka ya kama hanyar zuwa Madina domin hijira, kamar yadda Abdullahi ɗan Abbas ya ruwaito. [Dubi Ibn Jarir, *Jami'ul Bayan*, Juzu'i na 21, shafi na 198].

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tis'in da shida (96) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Hadiɗ*' kafin '*Suratur Ra'ad*'.

4. Adadin ayoyinta:
Adadin ayoyinta talatin da takwas ne (38) a lissafin mutanen Kufa. Amma a lissafin mutanen Madina da Makka da Sham talatin da tara (39) ne. A wurin mutanen Basra kuwa ayoyinta arba'in ne (40).

5. Babban Jigonta:
Zaburar da Musulmi a kan yaƙar kafirai da karya makirce-makircensu don Musulmi su ƙara ƙarfi.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Mafi yawan ayoyinta suna zaburar da Musulmi ne a kan su tashi su yaƙi kafiran da suke yaƙar su, don su sami gwaggwaɓan ladan masu jihadi.
• Ta buɗe da bayanin babban laifin mushirikai, watau hana mutane bin tafarkin Allah da kafirce masa, wanda zai sa lalle muminai su tashi su yaƙe su a kan haka.
• Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da muminai cewa ayyukan kafirai ba za su taɓa yin kyau ba kuma ba zai datar da su ba, nasararsa kuma tana ga muminai.
• Umarnin Allah ga muminai na su yaƙi kafirai da kuma bayanin tanadin gidan Aljanna da ni'imominta da ya yi musu.
• Yi wa mushirikai kashedi na aukuwar azabar Allah a kansu, irin wadda ta sauka a kan kafiran da suka gabace su bayan sun ƙaryata manzanninsa.
• Bayanin siffofin Aljanna da ni'imominta da siffofin wuta da azabar cikinta.
• Tsoratar da munafukai da cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai fallasa siffofinsu ga Annabi (ﷺ) da muminai, da kuma gargaɗin muminai da cewa kada su bari munafukai su ruɗe su ko su yaudare su.
• Ishara zuwa ga alƙawarin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa muminai na samun iko a nan gaba

Suratu Muhammad (1-3)

ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ أَضَلَّ أَعۡمَٰلَهُمۡ ١ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَءَامَنُواْ بِمَا نُزِّلَ عَلَىٰ مُحَمَّدٖ وَهُوَ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّهِمۡ كَفَّرَ عَنۡهُمۡ سَيِّـَٔاتِهِمۡ وَأَصۡلَحَ بَالَهُمۡ ٢ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱتَّبَعُواْ ٱلۡبَٰطِلَ وَأَنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّبَعُواْ ٱلۡحَقَّ مِن رَّبِّهِمۡۚ كَذَٰلِكَ يَضۡرِبُ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ أَمۡثَٰلَهُمۡ ٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Waɗanda suka kafirta suka kuma toshe hanyar Allah, to (Allah) Ya lalata ayyukansu.

2. Waɗanda kuwa suka yi imani suka kuma yi aiki nagari, kuma suka gaskata abin da aka saukar wa Muhammadu alhali kuwa shi ne gaskiya daga Ubangijinsu, sai (Allah) Ya kankare musu munanan ayyukansu, Ya kuma gyara musu halayensu.

3. Wannan (sakamako) kuwa saboda waɗanda suka kafirta sun bi ɓarna, waɗanda kuwa suka yi imani sun bi shiriya daga Ubangijinsu. Kamar haka ne Allah Yake buga wa mutane misalansu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da bayanin babban laifin kafirai na kafirce masa da hana mutane bin addininsa da Annabinsa yake kiran su zuwa gare shi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, ya lalata ayyukansu, watau ba za su sami wani lada ba a kan ayyukan ƙwarai da suka yi, kamar ciyar da mabuƙata da sada zumunci da ayyukan jin ƙai. Hakanan ayyukan da suka yi tuƙuru don ganin bayan Musulunci da Musulmi su ma sun tafi a banza, haƙansu bai cim ma ruwa ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kyakkyawan sakamakon waɗanda suka yi imani da Allah suka kuma yi kyawawan ayyuka, suka kuma yi imani da abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Manzonsa Muhammadu (ﷺ), watau Alƙur'ani kuma shi ne gaskiya daga Ubangijinsu; to su Allah ya kankare musu laifukansu, ba zai kama su da su ba, kuma ya gayara musu al'amuransu na duniya da na lahira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, dalilin wannan sakamako ga waɗannan ƙungiyoyi biyu, watau kafirai da muminai, shi ne saboda waɗanda suka kafirce wa Allah sun bi ɓarna, su kuma waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa sun bi gaskiyar da ta zo musu daga Ubangijinsu, don haka sakamakonsu ya bambanta. To kamar yadda Allah ya yi bayanin hukuncinsa game da waɗannan ƙungiyoyi biyu, hakanan yake ba wa mutane misalai domin a haɗa kowane abu da ɗan'uwansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Shar'anta wa Musulmi yaƙar kafiran da suke yaƙar su ko suke ɓata su addininsu, har sai sun sami 'yancinsu na bautar Allah shi kaɗai, maƙiyansu sun ajiye makamansu.

2. Shugaba na Musulmi yana da zaɓi a kan kafirai abokan gaba da za a kamo su a fagen yaƙi, idan ya ga dacewar ya sake su ba tare da an karɓi fansa daga wurinsu ba yana iya sakin su; idan kuma ya ga dacewar sai an karɓi fansa daga wurinsu ta kuɗi ko ta wani aiki da za a sa su yi wa Musulmi sannan a sake su, yana iya yin haka.

3. Da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ga dama da ya ba Musulmi nasara a kan kafirai a cikin karawa ɗaya, to amma saboda cikakkiyar hikimarsa sai bai yi musu haka ba, domin karawarsu da kafirai lokaci bayan lokaci ta zama jarrabawa ga Musulmi, don tantance mai imani na gaskiya daga mai ƙaryar da'awar imani, ko mai raunin imani daga cikinsu.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa waɗanda suka yi shahada a wajen ɗaukaka kalmarsa alƙawarin gafarar zunubansu da gyara musu rayuwarsu ta duniya da ta lahira. Gyara rayuwarsu ta ƙunshi kyakkyawan ambato da yabo a tsakanin muminai da kuma kula da iyalansu da suka bari da tsare su daga tozarta. A lahira kuwa zai ɗaukaka matsayinsu da girmama ladansu da sakamakonsu na Aljanna.

Suratu Muhammad (4-6)

فَإِذَا لَقِيتُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَضَرۡبَ ٱلرِّقَابِ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَثۡخَنتُمُوهُمۡ فَشُدُّواْ ٱلۡوَثَاقَ فَإِمَّا مَنَّۢا بَعۡدُ وَإِمَّا فِدَآءً حَتَّىٰ تَضَعَ ٱلۡحَرۡبُ أَوۡزَارَهَاۚ ذَٰلِكَ وَلَوۡ يَشَآءُ ٱللَّهُ لَٱنتَصَرَ مِنۡهُمۡ وَلَٰكِن لِّيَبۡلُوَاْ بَعۡضَكُم بِبَعۡضٖۗ وَٱلَّذِينَ قُتِلُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَلَن يُضِلَّ أَعۡمَٰلَهُمۡ ۝٤ سَيَهۡدِيهِمۡ وَيُصۡلِحُ بَالَهُمۡ ۝٥ وَيُدۡخِلُهُمُ ٱلۡجَنَّةَ عَرَّفَهَا لَهُمۡ ۝٦

4. To idan kuka haɗu da waɗanda suka kafirta sai ku sare wuyoyinsu har lokacin da kuka yi musu jina-jina, sai ku tsananta ɗauri; to bayan nan ko dai yafewa su tafi bayan (kun ribace su), ko kuma karɓar fansa har sai yaƙi ya lafa. Wannan abu haka yake, da kuma Allah Ya ga dama da Ya yi nasara a kansu (ko da ba yaƙi), sai dai kuma (Ya yi haka ne) don Ya jarrabi shashinku da shashi. Waɗanda kuwa aka kashe su a hanyar Allah, to ba zai taɓa lalata ayyukansa ba.

5. Zai shirye su Ya kuma kyautata halinsu.

6. Ya kuma shigar da su Aljannar da Ya sanar da ita gare su.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana umartar muminai da su tashi su yaƙi maƙiyansu kafirai waɗanda suka nuna tsangwama da ƙiyayya a gare su, har ta kai sun kore su daga garuruwansu da gidajensu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa idan sun haɗu da irin waɗannan kafiran a fagen yaƙi, to su tsaya tsayin daka su yi yaƙi da gaske ba ja da baya, su yi ta saran wuyansu suna kashe su har sai sun yi musu jina-jina sun karya lagonsu, to su kama su su ɗaure su tamau, daga nan suna da zaɓi:

a. Ko dai su sake su ba tare da sun karɓi fansa a hannunsu ba.

b. Ko kuma su karɓi fansa ta dukiya ko wani abu mai daraja sannan su sake su.
Watau za su zaɓi abin da ya fi dacewa da masalaha a lokacin.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su ci gaba da yaƙar kafirai, suna kama su har sai yaƙi ya zo ƙarshe sun ajiye makamansu an yi sulhu da su, ko kuma ma sun musulunta. Ya bayyana cewa, wannan abu da ya jarrabi muminai da shi na yaƙi da kafirai da ba da nasara a kansu ko kuma su kafirai su yi nasara a kan muminai, hukunci ne nasa, haka ya ga dama; da kuma ya so yin nasara a kan kafirai ko da babu yaƙi, to da ya yi, sai dai ya shar'anta jihadi ne don ya jarrabi mutane a junansu, ya tantance a cikin muminai wane ne zai yi yaƙin wane ne ba zai yi ba, ya kuma jarrabi kafiri da mumini. Idan mumini aka kashe ya shiga Aljanna, idan kuma shi muminin ya kashe kafiri ya shiga wuta. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, waɗanda aka kashe su wajen yaƙi don Allah, to ba zai lalata ayyukansu ba; zai karɓe su ya yi musu kyakkyawan sakamako a duniya da lahira, ya kuma datar da su ga bin hanyar gaskiya a rayuwarsu ta duniya, ya gyara musu al'amuransu, sannan a ranar alƙiyama ya shigar da su gidan Aljanna wadda tun a nan duniya ya riga ya bayyana musu siffofinta sun gane ta sosai, a lahira kuma ya shigar da su gidajensu da aka tanadar musu a Aljanna.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Muminai za su kuɓuta daga faɗawa wuta (yayin ƙetare Siraɗi) sai kuma a tsayar da su a kan wata gada tsakanin

Aljanna da wuta, sai a yi musu hukunci a junansu na zaluncin da ya kasance a tsakaninsu a duniya, har sai an tsaftace su an kuma tsarkake su, sai a ba su izinin shiga Aljanna. Na rantse da wanda ran Muhammadu yake hannunsa ɗayansu sai ya fi gane hanyar zuwa gidansa na Aljanna fiye da yadda ya kasance yana gane hanyar zuwa gidansa a duniya." [Bukhari #6535].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin taimaka wa muminai da ba su nasara amma da sharaɗin su ma su taimaki addininsa.

2. Tabbatar da dugadugai da tsayawa a kan kyakkyawar manufa bayan samun nasara, wata babbar baiwa ce daga Allah.

3. Nuna ƙiyayya da bijire wa wani hukunci na Allah kafirci ne.

Suratu Muhammad (7-9)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن تَنصُرُواْ ٱللَّهَ يَنصُرۡكُمۡ وَيُثَبِّتۡ أَقۡدَامَكُمۡ ۝٧ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَتَعۡسٗا لَّهُمۡ وَأَضَلَّ أَعۡمَٰلَهُمۡ ۝٨ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ كَرِهُواْ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأَحۡبَطَ أَعۡمَٰلَهُمۡ ۝٩

7. Ya ku waɗanda suka yi imani idan kuka taimaki Allah, to zai taimake ku, Ya kuma tabbatar da dugaduganku.

8. Waɗanda kuwa suka kafirce to kaiconsu, (Allah) kuma Ya lalata ayyukansu.

9. Wannan kuwa saboda cewa sun ƙi abin da Allah Ya saukar, sai Ya lalata ayyukansu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga waɗanda suka yi imani da shi da Manzonsa (ﷺ) suka rungumi aiki da karantarwarsa da su tashi su taimaki addininsa, su yi kira zuwa gare shi, su kuma yi jihadi don ɗaukaka kalmarsa, ya yi musu alƙawarin zai taimake su ya ba su nasara da rinjaye a kan abokan gabarsu, ya kuma tabbatar da dugadugansu, watau ya ba su juriya da haƙuri da jajircewa, ya hore musu duk hanyoyin cin nasara ta rayuwa.

Su kuma waɗanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa (ﷺ), to hallaka da hasara sun tabbata a kansu, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rushe duk ladan kyawawan ayyukansu da suka aikata, ba za su amfane su da komai ba a lahira. Hakanan duk wani aiki na makirci da suke ƙulla wa muminai a duniya don su ga bayansu, Allah ya lalata musu shi, ba za su taɓa samun nasarar karya Musulunci da Musulmi ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, dalilin da ya jawo musu wannan mummunan sakamako shi ne, saboda suna ƙyamar Alƙur'ani da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) sun bijire wa duk abin da ya ƙunsa na Tauhidi, watau kaɗaita Allah da bauta, sai Allah ya rushe duk ayyukansu, suka yi hasara duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tafiye-tafiye a bayan ƙasa wata hanya ce da ke ƙara wa mumini tsoron Allah da samun darussa masu amfani a rayuwarsa ta addini da ta duniya.

2. Babu abin da kafiri ya sa a gaba sai more rayuwar duniya kaɗai ba tare da tunanin lahirarsa ba. Amma mumini babbar manufa a rayuwarsa ita ce bautar Allah don samun yardarsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙyale kafirai ne ba tare da ya kama su da miyagun laifukansu a nan duniya ba, ba don sun gagare shi ba, domin a baya ya hallaka al'ummu da dama waɗanda sun fi na yanzu ƙarfi da yawan tarin dukiya.

4. Babu wani daidaito tsakanin mumini da kafiri ko mai bin dokokin Allah da mai saɓa masa, ko da kuwa Allah ya fifita kafiri ko fajiri da wani abu na jin daɗin duniya. A wurin Allah ba ɗaya suke ba, mumini shi ne masoyin Allah abin taimakonsa, kafiri kuwa zai ɗanɗani azabarsa ne.

5. Munin bin son zuciya da kauce wa hujjar da ta zo daga Allah.

Suratu Muhammad (10-14)

*أَفَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۖ دَمَّرَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡۖ وَلِلۡكَٰفِرِينَ أَمۡثَٰلُهَا ١٠ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ مَوۡلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَأَنَّ ٱلۡكَٰفِرِينَ لَا مَوۡلَىٰ لَهُمۡ ١١ إِنَّ ٱللَّهَ يُدۡخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يَتَمَتَّعُونَ وَيَأۡكُلُونَ كَمَا تَأۡكُلُ ٱلۡأَنۡعَٰمُ وَٱلنَّارُ مَثۡوٗى لَّهُمۡ ١٢ وَكَأَيِّن مِّن قَرۡيَةٍ هِيَ أَشَدُّ قُوَّةٗ مِّن قَرۡيَتِكَ ٱلَّتِيٓ أَخۡرَجَتۡكَ أَهۡلَكۡنَٰهُمۡ فَلَا نَاصِرَ لَهُمۡ ١٣ أَفَمَن كَانَ عَلَىٰ بَيِّنَةٖ مِّن رَّبِّهِۦ كَمَن زُيِّنَ لَهُۥ سُوٓءُ عَمَلِهِۦ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهۡوَآءَهُم ١٤

10. Yanzu ba za su yi tafiya a bayan ƙasa ba sai su duba yaya ƙarshen waɗanda suka gabace su ya kasance? Allah Ya hallaka su; kafirai kuma suna da (sakamako) kwatankwacinsa.

11. Wannan kuwa saboda lalle Allah ne Majiɓincin al'amuran waɗanda suka yi imani, lalle kuma su kafirai ba su da wani majiɓinci.

12. Lalle Allah Yana shigar da waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari gidajen Aljanna (waɗanda) ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu; waɗanda kuwa suka kafirta suna jin daɗi (a duniya), suna kuma ta ciye-ciye kamar yadda dabbobi suke yi, wuta ce kuma makomarsu.

13. Alƙaryu nawa ne waɗanda suka fi alƙaryarka wadda ta fitar da kai ƙarfi, Mun hallakar da su, don haka ba su da wani mai taimakon su.

14. Yanzu waɗanda suka kasance a kan hujja daga Ubangijinsu, sa yi daidai da waɗanda aka ƙawata musu mummuna aikinsu, suka kuma bi son zuciyarsu?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa mushirikai tayin cewa, ashe bai kamata su zagaya bayan ƙasa ba su gane wa idanunsu mummunan ƙarshen da mutanen da suka gabace su ya kasance yayin da suka ƙaryata manzanninsu suka kafirce wa Allah? Lalle Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su, ya yi rugu-rugu da gidajensu da dukiyoyinsu. Kuma kafirai na kowane lokaci da kowane wuri suna da mummunan ƙarshe irin wannan.
Su kuma muminai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai kuɓutar da su daga azabarsa, ya ba su lada mai yawa saboda shi ne mai taimakon su a koyaushe, amma kafirai da suka bijire wa Allah suka ƙi shari'arsa ba su da wani mai taimakon su ko jiɓintar al'amarinsu.
A lokacin da yaƙin Uhudu ya zo ƙarshe jagoran rundunar mushirkai a wannan lokaci, watau Abu Sufyan ya hau ƙololuwar dutse ya ƙwala wa Musulmai kira yana cewa: "Akwai Muhammadu a cikinku?" Sai Manzon

Allah (ﷺ) ya hana su amsa masa. Sai ya sake ƙwalla ihu ya ce: “A cikinku akwai ɗan Abu Kuhafa?” yana nufin Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) , sai ba wanda ya amsa masa. Sai ya sake cewa: “A cikinku akwai Umar ɗan Khaɗɗab?” Sai ba su amsa masa ba. Sai ya ce: “Amma waɗannan dai duk kun gama da su.” Yana faɗin haka sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya kasa haƙuri ya ce: “Ya kai maƙiyin Allah, duk waɗannan da ka ambata suna nan da ransu. Lalle Allah ya wanzar da abin da zai ci gaba da baƙanta maka rai.” Sannan Abu Sufyan ya ce: “Ɗaukaka ga gunki Hubal.” Sai Annabi (ﷺ) ya ce wa sahabbai: “Ba za ku ba shi amsa ba?” Sai suka ce: “Me za mu faɗa masa?” Sai ya ce: “Ku ce: 'Allah ne mafi ɗaukaka, mafi girma'.” Sannan Abu Sufyanu ya sake ɗaga muryarsa ya ce: “Muna da Uzza, ku kuma ba ku da Uzza.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ba za ku ba shi amsa ba?” Sai suka ce: “Me za mu faɗa masa?” Sai ya ce: “Ku ce masa: 'Allah ne majiɓincinmu, ku kuma ba ku da mai jiɓintar ku'.” [Bukhari #4043].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana babban sakamako da zai yi wa muminai a lahira, na shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashin manya-manyan gine-ginensu da lambunansu, don girmamawa a gare su saboda imaninsu da kyawawan ayyukansu. Su kuma waɗanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa ba abin da suka sa a gaba sai sharholiya a duniya da ciye-ciye da biye wa sha’awarsu kamar yadda dabbobi suke yi. To waɗannan a ranar alƙiyama wuta ce makomarsu inda za su tabbata a cikin azaba babu mai fitar da su daga cikinta.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya kasance yana cin abinci mai yawa sai ya musulunta, sai ya dawo yana cin ɗan abinci kaɗan, da aka faɗa wa Manzon Allah (ﷺ) abin da ya faru sai ya ce: “Lalle mumini yana cin abinci ne ta hanji ɗaya, kafiri kuwa yana ci ne ta ‘yan hanji bakwai.” [Bukhari #5397].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tsoratar da mushirikan Makka, a lokaci ɗaya kuma ya lallashi zuciyar Manzonsa (ﷺ) ya kwantar masa da hankalinsa da cewa, kada kafiran da suka fitar da shi daga mahaifarsa, Makka, su zaci sun gagari Allah ne; to su sani cewa a baya can an yi al’ummu masu yawa waɗanda sun dama su sun shanye a wajen ƙarfin jiki da na dukiya da yawan ‘ya’ya, amma da suka ƙaryata manzanninsu sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su, ba su kuma samu wani mai taimakon su ya kuɓutar da su daga hannunsa ba. Don haka su ma mutanen Makka su shiga taitayinsu, don idan Allah ya ga dama zai iya yi musu azaba irin wannan idan ba su yi imani ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna bambancin da ke tsakanin ɓangarorin biyu, watau muminai da kafirai, da cewa, wanda ya yi imani da Allah a kan hujja bayyananna da ta zo masa daga Ubangijinsa game da addininsa, ya rungumi bautar Allah, ba zai taɓa zama daidai da mutumin da Shaiɗan ya ƙawata masa mummunan aikinsa, ya bi son zuciyarsa, ya yi watsi da shiriyar Allah ba.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Masu shiga gidan Aljanna su ne masu taƙawa, watau aiki da umarnin Allah da guje wa haninsa.

2. Girman ni’imomi da tanadin da Allah ya yi wa bayinsa masu biyayya a gare shi.

3. Yayin da bayin Allah na ƙwarai suka yi haƙuri da bin soye-soyen zukatansu wajen more rayuwar duniya sai Allah ya yi musu sakayya da kowane irin kayan daɗi a gidan Aljanna a lahira.

4. Duk wani abin jin daɗi na more rayuwa a duniya akwai makamancinsa a lahira, sai dai na lahira ya zarce na duniya nesa ba kusa ba wajen daɗin ɗanɗano da ƙamshi da nagarta. Sun yi tarayya ne kawai a suna da kamanni na zahiri.

5. Babu wani daidaito tsakanin muminai ‘yan Aljanna da kafirai ‘yan wuta har abada.

Suratu Muhammad (15)
مَّثَلُ ٱلۡجَنَّةِ ٱلَّتِي وُعِدَ ٱلۡمُتَّقُونَۖ فِيهَآ أَنۡهَٰرٞ مِّن مَّآءٍ غَيۡرِ ءَاسِنٖ وَأَنۡهَٰرٞ مِّن لَّبَنٖ لَّمۡ يَتَغَيَّرۡ طَعۡمُهُۥ وَأَنۡهَٰرٞ مِّنۡ خَمۡرٖ لَّذَّةٖ لِّلشَّٰرِبِينَ وَأَنۡهَٰرٞ مِّنۡ عَسَلٖ مُّصَفّٗىۖ وَلَهُمۡ فِيهَا مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ وَمَغۡفِرَةٞ مِّن رَّبِّهِمۡۖ كَمَنۡ هُوَ خَٰلِدٞ فِي ٱلنَّارِ وَسُقُواْ مَآءً حَمِيمٗا فَقَطَّعَ أَمۡعَآءَهُمۡ ١٥

15. Kwatankwacin Aljannar da aka yi wa masu taƙawa alƙawari da ita shi ne, a cikinta akwai ƙoramu na ruwa ba gurɓatacce ba, da kuma ƙoramu na nono da ɗanɗanonsa bai canja ba, da ƙoramu na giya masu daɗi ga mashaya, da ƙoramu na tatacciyar zuma, kuma suna da kowane irin nau’i na ‘ya’yan itace da kuma gafara daga Ubangijinsu. Yanzu (masu waɗannan sa yi) daidai da waɗanda za su dawwama a cikin wuta a kuma shayar da su ruwa tafasasshe, sai ya yayyanke kayan cikinsu?

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kaɗan daga ɗimbin ni’imomin gidan Aljanna da ya tanadar wa masu bin dokokinsa, da cewa a cikinta akwai ƙoramu na ruwan daɗi wanda ba ya wari ko zartsi, da kuma ƙoramu na nono da ɗanɗanonsa bai canja ba da kuma wasu ƙoramu na giya mai daɗin kwankwaɗa ga masu shan ta, ba ta kuma sa maye ko ciwon kai. Sannan kuma akwai wasu ƙoramu na tatacciyar zuma da babu wani sofanen haki ko gurɓata a cikinta.

An karɓo daga Mu’awiya ɗan Haida (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “A cikin Aljanna akwai kogi na nono da kogi na ruwa da kogi na zuma da kogi na giya, sannan daga baya a keto da ƙoramu daga gare su.” [Ahmad #20052].

Haka kuma duk abin da muminai suke so na ‘ya’yan itatuwa za a kawo musu, ga kuma uwa-uba wata gafara ta musamman da za su samu daga Ubangijinsu. Shin masu irin wannan kyakkyawan sakamako za su yi daidai da wanda sakamakonsa shi ne dawwama a cikin wuta har abada, a kuma shayar da su tafasasshen ruwa wanda zai yayyanke musu kayan cikinsu?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mummunan halin munafukai na rashin nuna damuwa da wa’azin da suke sauraro da nuna izgili game da shi.

2. Tambayar da munafukai suke yi wa muminai game da abin da Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa tana iya ɗaukar ma’anar izgili da suka gare shi da nuna cewa yana yin maganar da ba a fahimtar abin da yake faɗa, ko kuma suka ga su kansu sahabbai da nuna cewa, su ne suke ɗaukar duk abin da Annabi (ﷺ) yake faɗa musu da muhimmanci har suke damuwa da sai sun kiyaye duk abin da yake faɗa.

3. Duk wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya toshe masa zuciyarsa alheri da ilimi mai amfani ba ya ratsa ta, to bin son zuciya ne zai mamaye ta.

4. Duk wanda ya riƙi wata shiriya ta Allah, to Allah zai yi ta ƙara masa shiriya a kan shiriya, domin duk wani kyakkyawan aiki yana haifar da wani kyakkyawan aiki irinsa.

5. Alƙiyama tana da alamu na kusantowarta, kuma wasu daga cikin alamominta sun daɗe da bayyana.

6. Idan alƙiyama ta zo babu wani da imaninsa ko tubansa zai amfane shi.

7. Falalar ilimi, kuma yana gaba da aiki, don haka ko kalmar Tauhidi ba za ta zauna ba sai da ilimi, shi ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara umartar sa da shi kafin kalmar Tauhidi da istigfari.

8. Duk da kasancewar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya gafarta wa Manzonsa (ﷺ) duk laifukansa waɗanda suka gabata da ma waɗanda ba su faru ba, to amma sai ya umarce shi da neman gafara domin ya nuna wa al'ummarsa muhimmancin yawan neman gafarar Allah.

Suratu Muhammad (16-19)
وَمِنْهُم مَّن يَسْتَمِعُ إِلَيْكَ حَتَّىٰٓ إِذَا خَرَجُواْ مِنْ عِندِكَ قَالُواْ لِلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلْعِلْمَ مَاذَا قَالَ ءَانِفًاۚ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ طَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهْوَآءَهُمْ ﴿١٦﴾ وَٱلَّذِينَ ٱهْتَدَوْاْ زَادَهُمْ هُدًى وَءَاتَىٰهُمْ تَقْوَىٰهُمْ ﴿١٧﴾ فَهَلْ يَنظُرُونَ إِلَّا ٱلسَّاعَةَ أَن تَأْتِيَهُم بَغْتَةً ۖ فَقَدْ جَآءَ أَشْرَاطُهَاۚ فَأَنَّىٰ لَهُمْ إِذَا جَآءَتْهُمْ ذِكْرَىٰهُمْ ﴿١٨﴾ فَٱعْلَمْ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ وَٱسْتَغْفِرْ لِذَنۢبِكَ وَلِلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِۗ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ مُتَقَلَّبَكُمْ وَمَثْوَىٰكُمْ ﴿١٩﴾

16. Daga cikinsu kuma akwai waɗanda suke sauraron ka, har lokacin da suka fita daga wurinka sai su ce da waɗanda aka bai wa ilimi: "Shin me ma ya ce ɗazu?" Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya toshe zukatansu suka kuma bi son ransu.

17. Waɗanda kuwa suka shiryu Ya ƙara musu shiriya, Ya kuma kimsa musu taƙawarsu.

18. Ai ba wani abu da suke sauraro sai alƙiyama ta zo musu farat ɗaya; to haƙiƙa alamominta sun zo. To ƙaƙa tunawar tasu za ta zame musu idan abin (alƙiyamar) ta zo musu ne?

19. To ka sani cewa, babu wani abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma ka nemi gafarar zunubanka da na muminai maza da mata, Allah kuma Yana sane da kai-kawonku (na rana) da kuma wurin kwanciyarku (da daddare).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fallasa munafukai yayin da suke halartar majalisin Manzon Allah (ﷺ) sanda yake wani bayani, sai su nuna suna sauraron sa amma kuma ba sa ba da hankalinsu a kan abin da yake faɗa don haka ba sa fahimtar komai, sai sun fita daga wajensa sai su riƙa tambayar waɗanda Allah ya ba wa ilimi, wai su faɗa musu mene ne Manzon Allah (ﷺ) yake cewa ne ɗazu? Don su nuna cewa su maganarsa ba ta dame su ba, don ba su ɗauke ta da wani muhimmanci ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, waɗannan mutane ya riga ya toshe zukatansu, babu wani alheri da zai shige su, domin sun zaɓi su bi son zuciyarsu, don haka idanuwansu suka makance ba sa ganin kowace gaskiya da ake nuna musu.
To amma waɗanda suka yi imani suka zaɓi su bi hanyar gaskiya, su bi abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da shi, to waɗannan Ubangijinsu zai ƙara musu shiriya da taƙawa, sai su yi aikin da zai kuɓutar da su daga fushin Allah da azabarsa.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar da cewa, su kafirai ba abin da suke sauraro sai alƙiyama ta zo musu kwatsam ba zato ba tsammani, sun manta da cewa alamomin alƙiyama sun riga sun bayyana, daga cikinsu akwai aiko da Manzo (ﷺ) akwai kuma tsagewar wata da ya faru a gaban idonsu. To duk waɗannan ba su ishe su wa'azi ba; to ta yaya kuma za su wa'azantu idan har alƙiyamar ta zo musu, rayuwarsu ta duniya ta zo ƙarshe? A lokacin babu sauran wani hanzari da za su bayar sai dai su ga sakamakon ayyukansu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar da Manzonsa (ﷺ) da ya sami ilimi na Tauhidi, watau sakankancewa a kan babu wani abin bauta da gaskiya sai Allah, sannan ya nemi gafarar zunubansa daga Allah ya kuma nema wa muminai maza da mata gafarar zunubansu daga Allah. Ya tabbatar masa cewa

yana sane da kai-kawon kowa da rana da wuraren komawarsu da daddare, babu abin da yake ɓuya a gare shi.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance yana cewa: "Ya Allah, ka gafarta mini kuskurena da rashin sanina da wuce iyaka cikin al'amarina da abin da kai ne ka fi ni saninsa. Ya Allah, ka gafarta mini laifin da na yi da wasa ko da gaske da kuskurena da gangancina. Duk waɗannan suna tare da ni." [Bukhari #6398 da Muslim #2719].

An karɓo daga Aliyyu ɗan Abu Ɗalib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance a ƙarshen sallarsa yakan ce: "Ya Allah, ka gafarta min abin da na gabatar da abin da na jinkirtar da abin da na ɓoye da abin da na bayyana da abin da na wuce iyaka a cikinsa da abin da kai ne ka fi ni saninsa, kai ne abin bautana, babu abin bauta da gaskiya sai kai." [Muslim #771].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Na rantse da Allah, lalle ni a kullum ina neman gafarar Allah ina tuba zuwa gare shi sau saba'in." [Bukhari #6307].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni da a fita jihadi shi yake bayyana muminai na gaskiya da munafukai a fili.

2. Munafukai mutane ne matsorata marasa ƙarfin hali, kuma masu raki.

3. Zuciyar munafukai lullubе take da cuta, babu abin da zai magance ta kuwa sai ikhlasi da imani na gaskiya.

4. Juya wa umarnin Allah baya da rashin yi masa biyayya shi ne yake jawo yaɗuwar ɓarna a bayan ƙasa da yanke zumunci a cikin al'umma.

5. Munin yanke zumunta da mummunan sakamakonsa.

Suratu Muhammad (20-23)
وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَوۡلَا نُزِّلَتۡ سُورَةٞۖ فَإِذَآ أُنزِلَتۡ سُورَةٞ مُّحۡكَمَةٞ وَذُكِرَ فِيهَا ٱلۡقِتَالُ رَأَيۡتَ ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ يَنظُرُونَ إِلَيۡكَ نَظَرَ ٱلۡمَغۡشِيِّ عَلَيۡهِ مِنَ ٱلۡمَوۡتِۖ فَأَوۡلَىٰ لَهُمۡ ٢٠ طَاعَةٞ وَقَوۡلٞ مَّعۡرُوفٞۚ فَإِذَا عَزَمَ ٱلۡأَمۡرُ فَلَوۡ صَدَقُواْ ٱللَّهَ لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۡ ٢١ فَهَلۡ عَسَيۡتُمۡ إِن تَوَلَّيۡتُمۡ أَن تُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَتُقَطِّعُوٓاْ أَرۡحَامَكُمۡ ٢٢ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُ فَأَصَمَّهُمۡ وَأَعۡمَىٰٓ أَبۡصَٰرَهُمۡ ٢٣

20. Waɗanda kuma suka yi imani suna cewa: "Me ya hana a saukar da wata sura (wadda za ta ba mu damar yin yaƙi)?" Sannan lokacin da aka saukar da wata sura mai ɗauke da hukunci aka kuma ambaci yaƙi a cikinta, sai ka ga waɗanda suke da raunin imani a zukatansu (watau munafukai), suna kallon ka kamar kallon wanda yake cikin magagin mutuwa. To abin da ya fiye musu.

21. (Shi ne) yin biyayya da magana mai kyau. To idan al'amarin yaƙi ya tabbata, to da za su nuna wa Allah gaskiyarsu, da ya fi musu alhairi.

22. Shin ba kwa ganin idan kuka ba da baya (daga bin Allah) sai ku yi ɓarna a bayan ƙasa, ku kuma yanke zumuntarku?

23. Waɗannan su ne waɗanda Allah Ya la'ance su, sai Ya kurumtar da su, Ya kuma makantar da ganinsu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin muminai na gaskiya da kuma halin munafukai waɗanda suke yin ƙaryar sun yi imani, da cewa su muminai koyaushe suna sauraron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sauko musu da ayoyi da suka ƙunshi umarni da yin wasu ayyuka komai wahalarsu, don su yi aiki da su, ko da kuwa umarni ne na yaƙi da kafirai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da zai saukar da wata sura mai ƙunshe da wani hukunci a cikinta a yi maganar yaƙi, to da sai an ga munafukai waɗanda zukatansu suka cika da kokwanto sun riƙa kallon Manzon Allah a firgice irin kallon mutumin da yake cikin magagin mutuwa, saboda ba abin da suka tsana irin a yi musu maganar fita wajen jihadi. Sai Allah ya yi musu alƙawarin narko na azaba wanda yake dab da ya auka musu saboda munafuncinsu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, su bi umarninsa su kuma faɗi maganar da ta dace, wannan shi ya fi musu alheri. Idan kuma aka wajabta musu yaƙi, kuma al'amarin ya tabbata da gaske babu ja da baya, to da za su nuna wa Allah gaskiyar imaninsu da shi, su kuma yi masa biyayya da wannan ya fi musu a kan su riƙa yin munafurci suna saɓa wa umarninsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da mutane za su bijire wa imani da yi masa biyayya, to babu abin da zai riƙa faruwa daga wajensu sai dai su yi ta yaɗa ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar kafirci da saɓon Allah, su kuma riƙa yanke zumuntarsu kamar yadda suka riƙa yi a lokacin jahiliyya kafin zuwan Musulunci. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, waɗanda suka siffantu da waɗannan miyagun siffofi ya la'ance su ya nisanta su daga rahamarsa, don haka sai ya kurumtar da su suka daina jin gaskiya ji na fahimta da miƙa wuya, ya kuma makantar da idanuwansu suka daina ganin gaskiya ballantana su bi ta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwaɗaitarwa game da tuntuntuni a kan ayoyin Alƙur'ani don samun kyakkyawar fahimtar su.

2. Rashin fahimtar ma'anonin Alƙur'ani don wa'azantuwa da su yana nuna cewa akwai rufi a kan zuciyar bawa.

3. Shaiɗan ne yake ƙawata wa bawa saɓon Allah da jefa masa burace-buracen ƙarya a zuciyarsa har sai ya kai shi ga yin ridda ya bar Musulunci.

4. Haɗa baki da waɗanda ba Musulmi ba don cutar da Musulunci da Musulmi yakan kai mutum zuwa ga ridda.

5. Yana daga cikin siffofin kafirai ƙin shari'ar Allah da ƙyamatar ta.

6. Lalacewar ayyukan ƙwarai da kafirai suka aikata saboda kafircinsu da ƙin bin abin da Allah ya saukar.

7. Duk yadda munafukai suka kai wajen ɓoye munafuncinsu sai an gano su an tona asirinsu.

8. Jarraba sunnar Allah ce don ya tantance tsakanin muminai da munafukai.

Suratu Muhammad (24-31)
أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلْقُرْءَانَ أَمْ عَلَىٰ قُلُوبٍ أَقْفَالُهَآ ﴿٢٤﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱرْتَدُّوا۟ عَلَىٰٓ أَدْبَـٰرِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلْهُدَى ٱلشَّيْطَـٰنُ سَوَّلَ لَهُمْ وَأَمْلَىٰ لَهُمْ ﴿٢٥﴾
ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ قَالُوا۟ لِلَّذِينَ كَرِهُوا۟ مَا نَزَّلَ ٱللَّهُ سَنُطِيعُكُمْ فِى بَعْضِ ٱلْأَمْرِ ۖ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ إِسْرَارَهُمْ ﴿٢٦﴾ فَكَيْفَ إِذَا تَوَفَّتْهُمُ ٱلْمَلَـٰٓئِكَةُ يَضْرِبُونَ

وُجُوهَهُمۡ وَأَدۡبَٰرَهُمۡ ٢٧ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمُ ٱتَّبَعُواْ مَآ أَسۡخَطَ ٱللَّهَ وَكَرِهُواْ رِضۡوَٰنَهُۥ فَأَحۡبَطَ أَعۡمَٰلَهُمۡ ٢٨ أَمۡ حَسِبَ ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ أَن لَّن يُخۡرِجَ ٱللَّهُ أَضۡغَٰنَهُمۡ ٢٩ وَلَوۡ نَشَآءُ لَأَرَيۡنَٰكَهُمۡ فَلَعَرَفۡتَهُم بِسِيمَٰهُمۡۚ وَلَتَعۡرِفَنَّهُمۡ فِي لَحۡنِ ٱلۡقَوۡلِۚ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ أَعۡمَٰلَكُمۡ ٣٠ وَلَنَبۡلُوَنَّكُمۡ حَتَّىٰ نَعۡلَمَ ٱلۡمُجَٰهِدِينَ مِنكُمۡ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَنَبۡلُوَاْ أَخۡبَارَكُمۡ ٣١

24. Yanzu ba za su yi tunani na basira ba (game da) Alƙur’ani ba, ko kuwa akwai wani rufi ne a kan zukatansu?

25. Lalle waɗanda suka yi ridda suka koma baya, bayan kuwa shiriya ta bayyana a gare su, to Shaiɗan ne ya ƙawata musu ya kuma yi musu shifta.

26. Wannan kuwa saboda lalle su, sun ce wa waɗanda suka ƙi bin abin da Allah Ya saukar: “Za mu bi ku a wasu al’amura.” Allah kuwa Yana sane da asiransu.

27. To yaya za su zama lokacin da mala’iku za su karɓi rayukansu suna dukan fuskokinsu da bayansu?

28. Wannan kuwa saboda lalle su, sun bi abin da yake fusata Allah suka kuma ƙi bin yardarsa, sai ya rusa ayyukansa.

29. Ko kuwa waɗanda suke da cuta a cikin zukatansu suna tsammanin cewa Allah ba zai fito da ƙulle-ƙullen zukatansu ba ne?

30. Kuma da Mun ga dama da tabbas Mun nuna maka su (watau munafukai), to tabbas da ka gane su da alamominsu. Kuma tabbas za ka iya gane su ta hanyar salon maganarsu. Allah kuma Yana sane da ayyukanku.

31. Kuma tabbas za Mu jarraba ku har sai Mun bayyana masu jihadi daga cikinku, da masu haƙuri, kuma za Mu bayyana halayenku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jawo hankalin masu bijire wa sauraron karatun Alƙur’ani da fahimtarsa da cewa, me zai hana su nutsu su yi tunani mai zurfi game da Alƙur’ani, domin yin haka zai taimaka musu wajen fahimtar sa, ya kuma sanya su dace da duk wani alheri, su tsira daga duk wani sharri? Ko kuwa zukatansu ne a rufe ruf babu ta inda alheri ko wa’azi ko tunatarwa za su shige su? Watau dai al’amarinsu ba zai wuce ɗayan abubuwan nan biyu ba:
Ko dai ba sa tsayawa su yi karatun ta-nutsu su fahimci abin da Alƙur’ani yake faɗa musu.
Ko kuma gaba ɗaya sun rasa hankulansu ne ba sa iya gane komai.
Kowanne ɗaya daga cikin biyun nan sharri ne ba alheri ba a gare su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin mutanen da suka yi ridda suka koma baya zuwa kafirci ko munafurci, bayan shiriya ta bayyana a gare su, hujjar Allah ta tabbata a kansu, sun gane gaskiyar Manzon Allah (ﷺ) sarai, to waɗannan mutane Shaiɗan ne ya ƙawata musu kafirci da munafurci, ya jefa musu dogon buri a zukatansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan mutane sun faɗa cikin wannan ɓatan ne, saboda sun haɗa kai da waɗanda suka ƙi Allah da Manzonsa (ﷺ) da wahayin da ya saukar masa, har ma suka faɗa wa mushirikai a ɓoye cewa, za su yi musu biyayya game da wasu al’amura idan sun taso, kamar daƙile mutane da hana su fita wajen yaƙi tare da Annabi (ﷺ) . Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, yana sane da duk abin da suke ɓoyewa da wanda suke bayyanawa, don haka zai tona asirinsu a wajen Manzonsa (ﷺ) duk sanda ya so.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da su da nuna musu cewa, idan suna zaton dabararsu a nan duniya za ta fisshe su, to yaya za su yi da kansu lokacin da mala'iku za su zo karɓar rayukansu suna dukan fuskokinsu da bayansu da gudumomin wuta duka mai tsanani? Wannan irin azaba kuwa da take jiran su lokacin mutuwarsu za ta same su ne saboda sun yarda su bi duk wani abu na kafirci da munafurci da yake fusata Allah, suka kuma ƙi bin duk abin da zai kusantar da su zuwa ga Ubangijinsu har su sami yardarsa, kamar imani da shi da biyayya ga Manzonsa (ﷺ), don haka Allah ya lalata ayyukansu kyawawa, kamar sadaka da taimakon gajiyayyu da sada zumunci.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi munafukai waɗanda zukatansu suke cike da shakka, shin suna tsammanin cewa Allah ba zai fallasa su ba ya fito da ƙulle-ƙullen da ke zukatansu a sarari? Lalle wannan zato nasu na banza ne domin ya saba wa hikimarsa ta bambance mai gaskiya da maƙaryaci, har a gane mumini na gaskiya da ɗan jabu, watau munafuki.
Saboda haka sai Allah ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, da ya ga dama da ya nuna masa munafukai ɗaya bayan ɗaya duk ya gane su da alamominsu, amma kuma bai yi haka ba don rufa wa bayinsa asiri da kuma gudun kada yin hakan ya jawo wa danginsu muminai wasu matsaloli. Amma duk da haka ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa zai iya gane su ta salon maganarsu wadda take cike da dungu da harshen damo. To amma Allah yana sane da ayyukan bayinsa duka, zai kuma yi musu sakayya a kai.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana babbar jarrabar da zai yi wa muminai, watau ya umarce su da yaƙar maƙiyansa, domin ya bayyana wa bayinsa su wane ne masu jihadi saboda shi masu kuma haƙuri a kan haka, ya kuma fito da mai gaskiya da maƙaryaci a fili.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan ayyukan kafirai ɓatattu ne ba su da lada a kansu saboda rashin yin imani da Allah da Manzonsa (ﷺ).

2. Hana mumini ya ɓata ayyukansa ya ƙunshi ɓata su bayan ya aikata su, ta hanyar gori ko ji-ji-da-kai ko fariya ko riya. Hakanan ya ƙunshi aikata wasu ayyuka na saɓon Allah waɗanda za su tauye masa kyawawan ayyukansa ko su rushe masa ladansu. Hakanan ya ƙunshi lalata aiki bayan an fara shi ta hanyar fasawa ko aikata abin da zai ɓata wannan aikin, kamar salla da abubuwan da suke ɓata ta ko azumi ko hajji da abubuwan da suke ɓata su.

3. Wasu malamai sun kafa hujja da wannan ayar ta 33 a kan haramcin katse wata farilla da aka fara, da karhancin katse wata nafila da aka shiga cikinta ba tare da samun abin da zai tilasta yin haka ba.

4. Idan har Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana ɓata ayyuka, to wannan ya nuna umarni da kyautata su, da cika su, da yin su kamar yadda ya dace.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya ƙin karɓar kafirai har sai idan sun mutu a kan kafirci. Amma idan suka tuba kafin su mutu, to Allah zai gafarta musu ya yi musu rahama ya kuma shigar da su Aljanna ko da kuwa sun daɗe cikin kafirci da yaƙar addininsa da saba masa. Wannan yana nuna yalwar rahamar Allah da falalarsa ga bayinsa.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa abubuwa uku kowanne ya kai ya sanya muminai su yi haƙuri kada su karaya:
Na farko, kasancewar su ne a sama, duk wasu dalilan cin nasara sun gama samun su, kuma ga shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu alƙawarinsa na gaskiya, domin mutum ba ya rauni sai dai idan ya zamanto shi ne a ƙasa, kuma ba ya da wani ƙarfi da yawan adadi.

Na biyu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tare da su, domin su muminai ne, Allah kuwa yana tare da muminai da taimakonsa da nasararsa da ƙarfafawarsa. Wannan zai ba su ƙarfin zuciya da ƙarfin hali wajen fuskantar magabtansu.
Na uku, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya rage musu komai na ayyukansu, zai ba su cikakken ladansu har ma ya ƙara musu daga cikin falalarsa, musamman ibadarsu ta jihadi. Idan bawa mumini ya san cewa Allah ba zai tozarta masa jihadinsa ba, to wannan zai ƙara masa ƙwarin gwiwa da karsashi.
Kowane ɗaya daga waɗannan abubuwa uku zai ƙara wa mumini ƙwarin gwiwa, to ina kuma duk ukun su haɗu tare da shi, babu shakka zai samu cikakken karsashi da ƙarfin zuciya.

Suratu Muhammad (32-35)
إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَشَآقُّواْ ٱلرَّسُولَ مِنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلۡهُدَىٰ لَن يَضُرُّواْ ٱللَّهَ شَيۡـٔٗا وَسَيُحۡبِطُ أَعۡمَٰلَهُمۡ ٣٢ ۞يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَلَا تُبۡطِلُوٓاْ أَعۡمَٰلَكُمۡ ٣٣ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ثُمَّ مَاتُواْ وَهُمۡ كُفَّارٞ فَلَن يَغۡفِرَ ٱللَّهُ لَهُمۡ ٣٤ فَلَا تَهِنُواْ وَتَدۡعُوٓاْ إِلَى ٱلسَّلۡمِ وَأَنتُمُ ٱلۡأَعۡلَوۡنَ وَٱللَّهُ مَعَكُمۡ وَلَن يَتِرَكُمۡ أَعۡمَٰلَكُمۡ ٣٥

32. Lalle waɗanda suka kafirta suka kuma toshe hanyar Allah, kuma suka saɓa wa Manzo bayan shiriya ta bayyana a gare su, to ba za su taɓa cutar Allah da komai ba, kuma zai lalata ayyukansu.

33. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku bi Allah, kuma ku bi Manzonsa, kada kuma ku ɓata ayyukanku.

34. Lalle waɗanda suka kafirta suka kuma toshe hanyar Allah, sannan suka mutu a halin suna kafirai, to Allah ba zai taɓa gafarta musu ba.

35. To kada ku raunana, kuma kada ku kirawo su zuwa sulhu, alhali ku ne a sama, Allah kuwa Yana tare da ku, kuma ba zai tauye muku ayyukanku ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa kafirai na Yahudawa masu hana mutane bin hanyar Allah suna kuma nuna tsananin ƙiyayyarsu ga Manzon Allah (ﷺ) bayan sun gano siffofinsa a cikin Attaura, kuma sun ga mu'ujizoji a hannunsa masu tabbatar da cewa shi Annabin Allah ne. To su sani cewa ba za su cuci Allah komai da kafircinsu ba, sai dai su cuci kawunansu, kuma duk wasu kyawawan ayyuka da suke taƙamar sun aikata Allah zai rusa su ba za su sami ladansu ba. Hakanan duk makirce-makircen da suke ƙullawa don ruguza addinin Allah ba za su yi nasara ba, Allah zai lalata su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga muminai waɗanda suka yi imani da Allah suka yi aiki da shari'arsa da lalle su yi masa biyayya su kuma yi wa Manzonsa (ﷺ) biyayya, su yi aiki da umarninsa su kuma guji haninsa, ya kuma gargaɗe su da kada su kuskura su lalata ayyukansu ta hanyar aikata kafirci ko munafunci ko yin riya.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Mu jama'ar sahabban Manzon Allah (ﷺ) mun kasance muna gani ko muna da'awar cewa, babu wani aiki mai kyau da za mu yi face an karɓa, har sai da wannan ayar ta sauka: "Ku bi Allah, ku bi Manzo, kada ku ɓata ayyukanku." Yayin da ta sauka sai kuma muke tambayar cewa: "Mene ne wannan abu da zai ɓata mana ayyukanmu?" Sai muka ce: "Su ne manyan zunubai da munanan ayyuka. Sai kuma muka ƙasance duk sanda muka ga wani ya aikata wani mummunan aiki na laifi sai mu ce: "Lalle ya hallaka." Har sai da faɗin Allah ya sauka inda yake cewa: "Lalle Allah ba ya gafarta a yi shirka da shi, yana kuma gafarta abin da bai kai wannan ba ga wanda ya ga dama." Da wannan ayar ta sauka sai muka daina faɗar waccan maganar, sai muka zamanto idan mun ga ɗaya daga cikinmu ya yi wani babban laifi sai mu riƙa jiye masa tsoro, idan kuma bai aikata babban zunubi ba sai mu riƙa yi masa kyakkyawan fata." [Al-Marwazi *Ta'azimu Kadaris Salat*, Juzu'i na 2, shafi na 646].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara jan kunnen kafirai da cewa idan har suka dage a kan kafircinsu, suka ci gaba da hana mutane bin hanyar Allah har suka mutu suna kafirci ba su tuba ba, to su sani Allah ba zai gafarta musu ba, sai ya kama su da miyagun laifukansu ya jefa su cikin azabarsa ta har abada.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafi gwiwar muminai ya umarce su da kada su karaya ko su yi rauni wajen fuskantar abokan gabarsu, ko su neme su da yin sulhu kafin su kafiran su nuna suna so a yi sulhu, alhalin kuma ya bayyana cewa, su ne a saman kafiran, Allah ya ba su rinjaye a kansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa yana tare da su da taimakonsa da dafawarsa, ba kuma zai taɓa tauye musu wani abu daga sakamakon kyawawan ayyukansu ba, sai ma dai ya ƙara musu daga falalarsa da karamcinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duniya ba komai ce a wurin Allah ba, sannan yawan damuwa da ita yakan shagaltar da bawa daga tuna lahira da makomarsa.

2. Bawa ba zai dace da samun kyakkyawan sakamako daga Allah ba har sai ya yi imani ya kuma yi taƙawa, watau bin umarninsa da guje wa haninsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya neman bayinsa su ba shi dukiyoyinsu kafin ya ba su ladan kyawawan ayyukansu, hakanan shi ma Manzon Allah (ﷺ) ba ya neman su biya shi lada a kan abin da yake isar musu na saƙon Allah, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai ɗora musu su ba da duk dukiyarsu da suka mallaka sadaka ba; abin da kawai ya ɗora wa masu wadatar cikinsu shi ne su fitar da wani ɗan kaso daga dukiyarsu don taimaka wa mabuƙatan cikinsu.

4. Munin ɗabi’ar rowa ga wanda Allah ya wadata shi da ni’imar duniya.

Suratu Muhammad (36-38)
إِنَّمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا لَعِبٞ وَلَهۡوٞۚ وَإِن تُؤۡمِنُواْ وَتَتَّقُواْ يُؤۡتِكُمۡ أُجُورَكُمۡ وَلَا يَسۡـَٔلۡكُمۡ أَمۡوَٰلَكُمۡ ٣٦ إِن يَسۡـَٔلۡكُمُوهَا فَيُحۡفِكُمۡ تَبۡخَلُواْ وَيُخۡرِجۡ أَضۡغَٰنَكُمۡ ٣٧ هَٰٓأَنتُمۡ هَٰٓؤُلَآءِ تُدۡعَوۡنَ لِتُنفِقُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۖ فَمِنكُم مَّن يَبۡخَلُۖ وَمَن يَبۡخَلۡ فَإِنَّمَا يَبۡخَلُ عَن نَّفۡسِهِۦۚ وَٱللَّهُ ٱلۡغَنِيُّ وَأَنتُمُ ٱلۡفُقَرَآءُۚ وَإِن تَتَوَلَّوۡاْ يَسۡتَبۡدِلۡ قَوۡمًا غَيۡرَكُمۡ ثُمَّ لَا يَكُونُوٓاْ أَمۡثَٰلَكُم ٣٨

36. Rayuwar duniya wasa ce da sharholiya kawai. Idan kuwa kuka yi imani kuka kiyaye dokokin Allah, to zai ba ku ladanku, ba kuma zai tambaye ku ku ba da dukiyoyinku (duka) ba.

37. Don ko idan da zai tambaye ku ita (dukiyar gaba ɗaya) Ya kuma nace muku, to da sai ku yi rowa, Ya kuma fito da ƙulle-ƙullen zukatanku.

38. To ga ku fa ku ɗin nan ana kiran ku don ku ciyar a hanyar Allah, to daga cikinku akwai masu yin rowa; wanda kuwa duk ya yi rowa, lalle ya yi wa kansa rowa ne. Allah kuma Mawadaci ne, ku ne mabuƙata. Idan kuwa kuka ba da baya to zai canja wasu mutanen ba ku ba, sannan ba za su zama kamar ku ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa, duniya ba a bakin komai take a wajensa ba, domin kuwa ita wasa ce da sharholiya kawai, don haka kada muminai su yarda ta shagaltar da su har su manta da jihadi domin Allah ko neman lahira, sannan su sani cewa, idan sun yi imani da Allah da Manzonsa (ﷺ) suka kuma kiyaye dokokin Allah ta hanyar aiki da umarninsa da guje wa haninsa,

to zai ba su ladansu cikakke ba da tawaya ba. Sannan ya sanar da su cewa, ba ya nufin ya matsa musu a kan abin da ya fi ƙarfinsu, don haka ne bai taɓa neman su da su bayar da dukiyarsu gaba ɗayanta ba, sai dai ya neme su da su fitar da ɗan wani kaso ƙanƙani daga cikinta na zakka da ta wajaba a kansu.
Saboda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san halin ɗan'adam da tsananin sonsa ga dukiya da rowa wajen fitar da ita, da zai neme su da su bayar da dukiyarsu gaba ɗaya ya kuma matsa musu a kan haka, to da sai su yi rowa, sai Allah ya fito da abin da yake cikin zukatansu na kwaɗayi da rowa da tsananin son dukiya, wannan ya sa ya tausaya musu bai nemi su ba da duka dukiyarsu ba.
A ayar ƙarshe kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗakar da muminai cewa, ga su suna ganin abin da yake faruwa a gabansu, inda akan kira su a nemi su ba da wani ɓangare na dukiyoyinsu don Allah, don kuma taimakon addininsa, to amma duk da haka sai a samu wasu rowa ta hana su su ba da wani abu, su manta da cewa duk wanda ya yi rowar ba da wani ɗan kaso kaɗan daga ckin dukiyarsa don Allah, to ba zai cuci kowa ba sai kansa, domin ya haramta wa kansa samun lada daga Allah, Allah kuwa shi cikakken mawadaci ne, ba ya da buƙatar komai a wurin kowa, kowa ne yake da buƙata a wurinsa a kowane lokaci a cikin dukkan al'amura. Don haka ya gargaɗi muminai da cewa idan suka bijire suka bar Musuluncin to yana iya hallaka su, ya kawo wasu mutane daban waɗanda ba su ba, sannan ba za su zama kamar su ba, sai dai su zama masu ɗa'a ga Allah da bin dokokinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sulhun Hudaibiyya da Annabi (ﷺ) ya yi da mushirikai buɗi ne babba kuma gagarumar nasara ce a tarihin Musulunci, domin a sanadiyyarsa ne nasarori suka samu kamar haka:
Na ɗaya, an sami zaman lafiya tsakanin al'ummun Larabawa a lokacin.
Na biyu, an cire hannun Kuraishawa daga shiga duk wani rikici da yaƙi da zai auku tsakanin Musulmi da sauran kafirai, kamar Yahudawa.
Na uku, an samar da wata dama ta yaɗa da'awa da kiran Musulunci na ko'ina, har ma a cikin su kansu Kuraishawan, wanda a da kafin wannan sulhu babu irin wannan damar.
Na huɗu, wannan sulhu ya ba wa jama'a da yawa damar shiga Musulunci bayan gabanin haka suna jin tsoron faɗa da Kuraishawa idan sun musulunta.
Na biyar, Imam Muhammad bin Shihab Az-Zuhri yana cewa: "Ba a taɓa samun buɗi da ya fi na *Sulhul Hudaibiyya* ba, domin ya ba wa mushirikai dama su gauraya da Musulmi su saurari maganganunsu, sai Musulunci ya kama zukatansu. A cikin shekara uku mutane da yawa sun karɓi Musulunci, Musulmi suka ƙara yawa da wannan." [*Al-Bagawi,* Juzu'i na 7, Shafi na 297].

2. Girman matsayin Annabi (ﷺ) a wurin Allah, don haka ya gafarta masa dukkan zunubinsa, saboda yawan biyayyarsa gare shi da yawan waɗanda suka shiga Musulunci a sanadiyyarsa da yawan haƙurinsa game da tsangwama da cutarwa da ya gamu da ita saboda Allah.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa gagarumar nasara da bai taɓa ba wa wani ɗan'adam ba tun kafuwar duniya, domin cikin ɗan ƙanƙanin lokaci sai ga addinin da ya zo da shi ya mamaye tsibirin Larabawa, har ya ƙetara ya shiga manya-manyan ƙasashe masu maƙotaka da shi, ya danna ya shiga ko'ina a duniya ya karya manyan daulolin da ake jin tsoronsu a fagen yaƙi

48-Suratul Fat'h

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan wannan Sura shi ne '*Suratul Fat'h'*. Ba a san ta da wani suna ba bayan wannan. An sa mata wannan suna ne saboda ta ƙunshi bayani a kan gagarumar nasara da Allah ya ba wa Manzonsa (ﷺ) a dalilin *Sulhul Hudaibiyya* a shekara ta shida bayan hijira.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya*, domin ta sauka bayan hijirar Manzon Allah (ﷺ), amma ba a Madina ta sauka ba; ta sauka ne a wani wuri da ake kira da *Kura'ul Gamim* da ke tsakanin Makka da Madina, yana kuma cikin lardin Makka ne, kuma ta sauka da daddare.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ɗari da goma sha uku (113) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratus Saffi*' kafin '*Suratut Tauba*'.

4. Adadin ayoyinta:
Ayoyinta ishirin da tara ne (29).

5. Dalilin Saukarta:
An karɓo daga Sahlu ɗan Hunaif (Allah ya kara masa yarda), ya kasance a ranar yaƙin Siffin (tsakanin mutanen Iraƙi da mutanen Sham) yana cewa: "Ku tuhumi kawunanku, haƙiƙa na gan mu a ranar *Sulhul Hudaibiyya*, watau lokacin da Annabi (ﷺ) ya ƙulla yarjejeniyar dakatar da yaƙi tsakaninsa da mushirikan Ƙuraishawa. Da mun samu damar yin yaƙi a wannan lokacin da mun yaƙe su. Umar (Allah ya kara masa yarda) ya je ga Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Shin ba mu ne a kan gaskiya ba su kuma a kan ƙarya?" Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Haka ne mu ne." Ya ce: "Shin waɗanda aka kashe namu ba suna Aljanna ba, su kuma nasu suna wuta?" Manzon Allah (ﷺ) ya amsa masa cewa haka abin yake. Sai Umar ya ce: "To me ya sa za mu yarda da wulaƙanci a addininmu, mu koma Madina ba tare da Allah ya yi hukunci tsakaninmu da su ba?" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya ɗan Khaɗɗab, lalle ni Manzon Allah ne, kuma Allah har abada ba zai tozarta ni ba." Sai Umar (Allah ya kara masa yarda) ya koma cike da fushi, sai ya kasa haƙura ya tafi wurin Abubakar ya ce: "Ya Abubakar, shin ba mu ne a kan gaskiya ba su kuma a kan ƙarya?" Abubakar ya ce: "Haka ne mu ne." Umar ya ce: "Shin waɗanda aka kashe namu ba suna Aljanna ba, su kuma nasu suna wuta?" Abubakar (Allah ya kara masa yarda) ya amsa masa cewa haka abin yake. Sai ya ce: "To me ya sa za mu yarda da wulaƙanci a addininmu?" Sai Abubakar ya amsa masa da cewa: "Ya ɗan Khaɗɗab, lalle shi Manzon Allah ne, kuma har abada Allah ba zai tozarta shi ba." Sai '*Suratul Fathi*' ta sauka, sai Manzon Allah (ﷺ) ya aika aka kirawo Umar, ya karanta masa ita. Sai Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Ya Manzon Allah, shin sulhu buɗi ne?" Annabi (ﷺ) ya ce masa: "Ƙwarai kuwa." [Bukhari #3182 da Muslim #1785].

6. Falalarta:
An karɓo daga Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Mun kasance tare da Manzon Allah (ﷺ) a wata tafiya, sai na tambaye shi game da wani abu har sau uku amma bai ba ni amsa ba, sai a raina na ce: "Mahaifiyarka ta yi wabinka ya kai ɗan Khaɗɗab, ka matsa wa Manzon Allah (ﷺ) da tambaya har sau uku amma bai amsa maka ba." Sai na kaɗa raƙumina da sauri na wuce gaban mutane, na kuma ji tsoron kada Alƙur'ani ya sauka a kaina, ba da jimawa ba sai na ji mai kira yana kira na, sai na koma ina cike da zaton cewa wani abu na Alƙur'ani ya sauka game da ni. Sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle daren jiya an saukar mini da wata sura wadda na fi so fiye da duniya da abin da yake cikinta." Sai ya karanta wannan Surar. [Bukhari #4177].

7. Babban Jigonta:
Surar ta ƙunshi bayani ne a kan alƙawarin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Annabi (ﷺ) da muminai na samun buɗi da nasara da kafuwar addinin Musulunci.

8. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Yi wa Musulmi albishir da cewa nasara tasu ce, kuma sulhun Hudaibiyya ƙarshensa alheri ne gare su.
• Nuna babban matsayin Annabi (ﷺ) a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da alƙawarin da ya yi masa na ba shi nasarori ɗaya bayan ɗaya.
• Kyakkyawan yabo ga muminai waɗanda suka mara wa Manzon Allah (ﷺ) baya, suka yi masa mubaya'a. Allah kuma ya ba da misalinsu a littafin Attaura da Linjila.
• Ambaton mubaya'ar Hudaibiyya da bayanin girman darajar waɗanda suka halarce ta.
• Kunyata waɗanda suka ƙi halartar mubaya'ar Hudaibiyya daga cikin mutanen ƙauyuka da siffanta su da tsoro da munana wa Allah zato da yi wa Manzon Allah (ﷺ) ƙarya da hana su damar halartar yaƙin Khaibara. Sannan aka sanar da su cewa za a sake kiran su domin su halarci wani yaƙin, to idan sun amsa kira sun halarta sai a gafarta musu laifin ƙin halartar mubaya'ar Hudaibiyya da suka yi.
• Yi wa Annabi (ﷺ) alƙawarin samun wani fatahin wanda kuma wani fatahin mai girma zai biyo bayansa sai kuma *fathu Makka*.

Suratul Fat'h (1-3)
إِنَّا فَتَحۡنَا لَكَ فَتۡحٗا مُّبِينٗا ۝١ لِّيَغۡفِرَ لَكَ ٱللَّهُ مَا تَقَدَّمَ مِن ذَنۢبِكَ وَمَا تَأَخَّرَ وَيُتِمَّ نِعۡمَتَهُۥ عَلَيۡكَ وَيَهۡدِيَكَ صِرَٰطٗا مُّسۡتَقِيمٗا ۝٢ وَيَنصُرَكَ ٱللَّهُ نَصۡرًا عَزِيزًا ۝٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Lalle Mu ne Muka yi maka buɗi, buɗi mabayyani.

2. Don Allah Ya gafarta maka abin da ya gabata na zunubinka, da kuma wanda ya jinkirta, Ya kuma cika maka ni'imarsa, kuma Ya shiryar da kai hanya madaidaiciya.

3. Allah kuma zai taimake ka da nasara mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa ya yi masa gagarumin buɗi, ya ba shi nasara a kan abokan gabarsa ta hanyar yin sulhun Hudaibiyya, watau yarjejeniyar da Musulmi suka ƙulla da mushirikan Makka a shekara ta shida wadda ta ƙunshi dakatar da yaƙi a tsakaninsu na tsawon shekara goma, kuma Annabi (ﷺ) da sahabbansa suka haƙura da yin umara a wannan shekara sai shekara mai zuwa. Yarjejeniyar ta haɗa da duk waɗanda suke son ƙulla ƙawance da Manzon Allah (ﷺ)

suna iya ƙullawa, hakanan masu son su yi ƙawance da Kuraishawa su ma suna iya yi. Kuma duk wanda ya gudu daga Makka zuwa Madina Annabi (ﷺ) zai dawo musu da shi, su kuma ba za su dawo da duk mutumin da ya yi ridda ya gudo daga Madina zuwa Makka ba. Duk waɗannan sharuɗɗa kuma Annabi (ﷺ) ya karɓe su, ya ƙulla sulhu da mushirikan Kuraishawa a kansu, tare da cewa ba su yi wa da dama daga cikin Musulmi daɗi ba, amma suka haƙura suka yi wa Manzon (ﷺ) Allah biyayya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi wa Manzonsa (ﷺ) wannan ne domin ya gafarta masa zunubinsa da ya gabaci wannan buɗin da wanda ya jinkirta bai faru ba sai daga baya. Sannan kuma ya cika masa ni'imarsa da taimakon addininsa, ya kuma shiryar da shi hanya madaidaiciya wadda babu karkata a cikinta, ita ce Musulunci.

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: "Annabi (ﷺ) ya kasance yana tsayuwar dare har dugadugansa su riƙa tsattsagewa. Sai A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce masa: "Me ya sa kake yin haka ne ya Manzon Allah, alhali Allah ya gafarta maka abin da ya gabata na zunubanka da abin da ya jinkirta?" Sai ya ce: "Yanzu ba kya fatan in kasance bawa mai yawan godiya?" Yayin da ya yi ƙiba sai ya riƙa sallar a zaune, idan ya yi nufin yin ruku'u sai ya tashi ya ɗan yi karatu sai ya yi ruku'u." [Bukhari #4837].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi masa alƙawarin ba shi cikakkiyar nasara a kan abokan gabarsa, wanda hakan ya sa Musulunci ya yi ƙarfi sosai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Natsuwar zuciya alama ce ta imani, domin shi ne yake cika zuciya da dangana da komawa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Imani yana ƙaruwa yana kuma raguwa.

3. Komai da ke sammai da ƙasa Allah yana iya amfani da shi a matsayin rundunarsa don ɗaukaka addininsa da karya maƙiyansa, sai dai kawai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tafiyar da komai cikin hikimarsa da tsarinsa wanda sunnarsa ta gudana a kansa.

4. Babban rabo da bawa zai samu daga Ubangijinsa shi ne shiga gidan Aljanna da kankare masa zunubai irin waɗanda Allah yake kama masu su da azabarsa.

5. Fara gabatar da munafukai maza da mata a kan mushirikai maza da mata yana nuna girman haɗarin munafukai ga muminai, domin mumini zai iya ɗaukar matakin kare kansa daga maƙiyinsa na sarari, amma shi munafuki a ɓoye yake koyaushe ana mu'amala da shi, don haka zai iya bayyana sirrin muminai ga maƙiyansu. Kuma wannan, har ila yau yana nuna sun fi mushirikai shiga tsananin azaba.

6. Haɗarin munana zato ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Allah yana mu'amalantar bayinsa ne gwargwadon zaton da suke masa.

Suratul Fat'h (4-7)
هُوَ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ ٱلسَّكِينَةَ فِى قُلُوبِ ٱلْمُؤْمِنِينَ لِيَزْدَادُوٓاْ إِيمَٰنًا مَّعَ إِيمَٰنِهِمْ ۗ وَلِلَّهِ جُنُودُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمًا ۝٤ لِّيُدْخِلَ ٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَيُكَفِّرَ عَنْهُمْ سَيِّـَٔاتِهِمْ ۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عِندَ ٱللَّهِ فَوْزًا عَظِيمًا ۝٥ وَيُعَذِّبَ

ٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ وَٱلۡمُشۡرِكَٰتِ ٱلظَّآنِّينَ بِٱللَّهِ ظَنَّ ٱلسَّوۡءِۚ عَلَيۡهِمۡ دَآئِرَةُ ٱلسَّوۡءِۖ وَغَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ وَلَعَنَهُمۡ وَأَعَدَّ لَهُمۡ جَهَنَّمَۖ وَسَآءَتۡ مَصِيرٗا ٦ وَلِلَّهِ جُنُودُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمٗا ٧

4. Shi ne wanda Ya sanya nutsuwa a zukatan muminai don su ƙara imani a kan imaninsu. Rundunonin sammai da ƙasa kuma na Allah ne, kuma Allah Ya kasance Masani ne, Mai hikima.

5. (Ya yi haka ne) don Ya shigar da muminai maza da mata gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu suna masu dawwama a cikinsu, Ya kuma kankare musu laifukansu. Wannan kuwa ya kasance babban rabo ne a wurin Allah.

6. Ya kuma azabtar da munafukai maza da mata, da mushirikai maza da mata, masu munana zato ga Allah. Mummunar azaba ta koma a kansu; kuma Allah Ya yi fushi da su, Ya kuma la'ance su, Ya kuma tanadar musu Jahannama; makoma kuwa ta munana.

7. Kuma rundunonin sammai da ƙasa na Allah ne. Allah kuwa Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ni'imar da ya yi wa muminai bayan gudanar da sulhu tsakanin Manzonsa (ﷺ) da mushirikan Kuraishawa, sulhun da sharuɗɗansa ba su yi wa muminai daɗi ba, to amma Allah ya sanar da Manzonsa manyan hikimomin da suke ƙunshe cikinsa, su kuma muminai sai ya saukar musu da natsuwa a zukatansu, don hankalinsu ya kwanta, kuma imaninsu ya ƙaru a kan wanda suke da shi, kuma ya nuna musu cewa, ba su nasara da rinjaye a kan kafirai a wannan lokaci ba wani abu ne mai wuya a wurin Allah ba, domin rundunonin sammai da na ƙasa duk nasa ne, ƙarƙashin ikonsa suke, to amma yana zartar da komai ne cikin hikima da ilimi, domin ya tabbata shi masanin komai ne, mai hikima cikin dukkan ayyukansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi wa muminai ni'imar natsuwa a zukatansu da ƙarin imani a kan imaninsu domin ya shigar da su, mazansu da matansu cikin gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu, ya kuma kankare musu laifukansu ba zai kama su da su ba, wannan sakamako kuwa shi ne babban rabo da bawa zai samu daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Su kuma munafukai mazansu da matansu da mushirikai mazansu da matansu masu yi wa Allah mummunan zato cewa, ba zai taimaki addininsa ba, kuma ba zai ɗaukaka kalmarsa ba, to duk waɗannan a kansu kaɗai mummunan bala'i zai dawo na mugun zaton da suke yi wa Allah, kuma Allah ya yi fushi da su saboda kafircinsu da mummunan zatonsu, ya kuma la'ance s; ba su ba samun rahamarsa, kuma a lahira ya yi musu tanadin wutar Jahannama wadda za su shige ta su dawwama a cikinta har abada, makoma kuwa ta munana idan har ta zamanto wutar Jahannama ce.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar wa muminai cewa babu abin da zai gagare shi, domin rundunonin sammai da ƙasa duk nasa ne, a ƙarƙashin ikonsa suke, kuma shi ya tabbata mabuwayi ne babu abin da zai fi ƙarfinsa, mai hikima ne kuma cikin halittarsa da ƙaddararsa da tsarinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman martabar Manzon Allah (ﷺ) da wajabcin Musulmi ya girmama shi ya tsare martabarsa.

2. Falalar sahabban Annabi (ﷺ) waɗanda suka halarci mubaya'ar Hudaibiyya, kuma su ne mafi alherin waɗanda suke bayan ƙasa.

3. Tabbatar wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) siffar ‘Hannu’ wadda siffa ce ta Zatinsa, ana kuma tabbatar masa da ita ba tare da kwatance ko kamanceceniya da wata siffa ta mahaluƙi ba, ba kuma tare da canza mata ma’ana ba, watau a yi mata wani tawili.

4. Cikar wadatuwar Allah, don ba shi da buƙatar komai a wurin bayinsa, yana yi musu umarni da hani ne don amfanin kansu ba nasa ba.

Suratul Fat’h (8-10)

إِنَّآ أَرۡسَلۡنَٰكَ شَٰهِدٗا وَمُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ٨ لِّتُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتُعَزِّرُوهُ وَتُوَقِّرُوهُۚ وَتُسَبِّحُوهُ بُكۡرَةٗ وَأَصِيلًا ٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُبَايِعُونَكَ إِنَّمَا يُبَايِعُونَ ٱللَّهَ يَدُ ٱللَّهِ فَوۡقَ أَيۡدِيهِمۡۚ فَمَن نَّكَثَ فَإِنَّمَا يَنكُثُ عَلَىٰ نَفۡسِهِۦۖ وَمَنۡ أَوۡفَىٰ بِمَا عَٰهَدَ عَلَيۡهُ ٱللَّهَ فَسَيُؤۡتِيهِ أَجۡرًا عَظِيمَۢا ١٠

8. Lalle Mu Muka aiko ka don ka zama sheda kuma mai albishir mai gargaɗi.

9. Don (ku mutane) ku yi imani da Allah da Manzonsa ku kuma taimake shi (wato Annabinsa), kuma ku girmama shi, ku kuma tsarkake Shi (wato Allah) safe da yamma.

10. Lalle waɗanda suka yi maka mubaya’a Allah kawai suke yi wa mubaya'a, Hannun Allah yana saman hannayensu. To duk wanda ya warware, to kansa kawai ya warware wa, wanda kuwa ya cika abin da ya yi wa Allah alƙawarinsa, to ba da daɗewa ba za Mu ba shi lada mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana martabar Manzonsa (ﷺ) da matsayinsa a cikin al’umma da cewa, ya aiko Manzonsa Annabi Muhammadu (ﷺ) domin ya zama mai yi wa al’ummarsa shaida ranar alƙiyama cewa, ya isar musu da saƙon Allah, ya bayyana musu duk wani alheri don su aikata shi, ya kuma nuna musu duk wani sharri don su guje shi, ya kuma zama mai yi wa muminai albishir da abin da Allah ya tanadar musu a duniya na samun nasara da kafuwa, da kuma abin da ya tanadar musu a lahira na ni’imar gidan Aljanna, sannan mai gargaɗi ga kafirai game da ƙaskanci da karaya a fagen yaƙi a hannun muminai da kuma abin da ya tanadar musu a lahira na azaba mai raɗaɗi da take jiran su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa, ya yi musu haka ne don su yi imani da Allah da Manzonsa, su kuma girmama Manzonsa (ﷺ) tare da darajta shi, su kuma tsarkake Allah da tasbihi safe da yamma.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falalar sahabban da suka yi wa Manzon Allah (ﷺ) mubaya’a a Hudaibiyya a shekara ta shida bayan hijira zuwa Madina, yayin da ya aika Usman ɗan Affan zuwa ga Kuraishawa don ya shaida musu cewa, Annabi bai zo da niyyar ya yaƙe su ba, ya zo ne da niyyar ya yi umara kaɗai, don haka su ƙyale shi ya shiga garin Makka don gudanar da abin da ya zo dominsa, watau umara. Sai aka zo wa Manzon Allah (ﷺ) da labarin cewa Kuraishawa sun kashe Usman (Allah ya ƙara masa yarda), sai Manzon Allah (ﷺ) ya tara sahabbansa da suke tare da shi, waɗanda adadinsu ya kai mutum dubu da ɗari huɗu, dukkansu suka yi masa mubaya’a a kan jajircewa wajen yaƙi da Kuraishawa, ko su mutu ko su yi rai, ba gudu ba ja da baya. Annabi (ﷺ) ya ɗora tafin hannunsa na dama a kan na hagu ya ce wannan na Usman ne. Waɗannan su ne waɗanda ake ce wa ma’abota mubaya’ar ƙarƙashin bishiya ko kuma *‘Bai’atur Ridhwan’*, watau mubaya’ar samun yardar Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa cewa duk waɗanda suka yi masa muba’aya, to Allah suka yi wa, domin shi ne ya ba su umarnin su yaƙi mushirikai, kuma shi ne mai yi musu sakayya a kan haka. Allah ya tabbatar musu da cewa, hannunsa yana saman hannayensu lokacin da suke yin wannan mubaya’ar, don haka ya san komai babu abin da zai ɓuya gare shi.

An karɓo daga Al-Bara ɗan Azib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Ku kuna ɗaukar buɗi shi ne buɗe Makka, babu shakka buɗe Makka buɗi ne, amma mu muna ɗaukar buɗi shi ne ‘Bai’atur Ridhwan’ a ranar Hudaibiyya.” [Bukhari #3919].

An karɓo daga Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa mana a ranar Hudaibiyya cewa: “Ku ne mafi alherin mutanen da ke bayan ƙasa.” [Bukhari #3923 da Muslim #1856].

An karɓo daga Yazid ɗan Abu Ubaid (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na tambayi Salamatu ɗan Akwa’u (Allah ya ƙara masa yarda) cewa, a kan mene ne kuka yi wa Manzon Allah mubaya’a a ranar Hudaibiyya? Sai ya ce: "A kan mutuwa." [Bukhari #6780 da Muslim #1860].

An karɓo daga Jabir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Ya ji Ummu Mubasshir, (Allah ya ƙara mata yarda), tana cewa, ta ji Annabi (ﷺ) a wajen Hafsatu (Allah ya ƙara mata yarda), yana cewa: “In sha Allah, babu mutum ɗaya daga cikin mutanen da suka yi masa mubaya’a a ƙarƙashin bishiya da zai shiga wuta.” [Muslim #2469].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, yana sane da komai, don haka duk wanda ya warware mubaya’arsa bai cika alƙawarin da ya yi wa Allah na taimaka wa addininsa ba, to ya sani cewa kansa ya cuta ba Allah ba; wanda kuwa ya cika alƙawarin da ya yi wa Allah na taimaka wa addininsa, to Allah zai ba shi lada mai girma shi ne gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bijirewar da wasu Larabawan ƙauye suka yi na ƙin zuwa Makka tare da Manzon Allah (ﷺ) yayin da ya neme su da yin haka, kamar ƙabilun Ghifar da Muzaina da Juhaina da Ashja da Aslam. Ya nemi su fito don kada Kuraishawa su tare shi da yaƙi ko su hana shi zuwa ga Ɗakin Allah. To amma da yawa daga cikinsu sai suka ƙi fita tare da shi, suka kawo masa uzurori na ƙarya da suka shagaltar da su suka hana su fita.

2. Da yawa akan samu mutanen da za su riƙa maganar neman gafarar Allah, amma a aikace ba da gaske suke yi ba, domin sun ƙi gyara ayyukansu su tuba zuwa ga Allah.

3. Yi wa muminai mummunan zato yayin da suke ƙoƙarin aikata wani aikin alheri da tunanin Allah ba zai ba su nasara ba ɗabi’a ce ta munafukai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuwa ba ya tozarta bayinsa yayin da suke ƙoƙarin bin umarninsa da aikata abin da zai jawo musu yardarsa.

Suratul Fat’h (11-14)

سَيَقُولُ لَكَ ٱلۡمُخَلَّفُونَ مِنَ ٱلۡأَعۡرَابِ شَغَلَتۡنَآ أَمۡوَٰلُنَا وَأَهۡلُونَا فَٱسۡتَغۡفِرۡ لَنَاۚ يَقُولُونَ بِأَلۡسِنَتِهِم مَّا لَيۡسَ فِي قُلُوبِهِمۡۚ قُلۡ فَمَن يَمۡلِكُ لَكُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيۡـًٔا إِنۡ أَرَادَ بِكُمۡ ضَرًّا أَوۡ أَرَادَ بِكُمۡ نَفۡعَۢاۚ بَلۡ كَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرًا ١١ بَلۡ ظَنَنتُمۡ أَن لَّن يَنقَلِبَ ٱلرَّسُولُ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَ إِلَىٰٓ أَهۡلِيهِمۡ أَبَدٗا وَزُيِّنَ ذَٰلِكَ فِي قُلُوبِكُمۡ وَظَنَنتُمۡ ظَنَّ ٱلسَّوۡءِ وَكُنتُمۡ قَوۡمَۢا بُورَۢا ١٢ وَمَن لَّمۡ يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ فَإِنَّآ أَعۡتَدۡنَا لِلۡكَٰفِرِينَ سَعِيرٗا ١٣ وَلِلَّهِ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ يَغۡفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورٗا رَّحِيمٗا ١٤

11. Waɗanda suka ƙi fita da kai daga cikin mutanen ƙauye za su ce maka: “Dukiyoyinmu da iyalinmu ne suka shagaltar da mu, sai ka nema mana gafara.” Da harsunansu suna faɗar abin da ba ya cikin zukatansu. Ka ce: “To wa zai amfana muku wani abu ne a wajen Allah idan Ya yi nufin ku da cutuwa, ko kuma Ya yi nufin ku da alhairi?” A’a, Allah yana sane da abin da kuka kasance kuna aikatawa.

12. “A’a, ku dai kun zaci cewa Manzo da muminai ba za su komo wajen iyalinsu ba har abada, aka kuma ƙawata wannan a cikin zukatanku, kuka kuma yi mummunan zato, kuma kun kasance mutane halakakku.”

13. Duk kuwa wanda bai yi imani da Allah da Manzonsa ba, to lalle Mu Mun tanadi wutar Sa’ira ga kafirai.

14. Kuma mulkin sammai da ƙasa na Allah ne. Yana yin gafara ga wanda Ya ga dama, Yana kuma azabtar da wanda Ya ga dama. Allah kuwa Ya kasance Mai gafara ne, Mai rahama.

A waɗannan ayoyi kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zargi wasu mutanen ƙauye da suka ƙi fita zuwa Makka tare da Manzonsa (ﷺ); yayin kuma da ya tuhume su a kan haka sai suka riƙa cewa, kula da dukiyoyinsu da ‘ya’yansu ne suka shagaltar da su har ba su sami damar fita tare da shi ba, don haka suna roƙon sa da ya nema musu gafarar zunubansu a wurin Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, ƙarya suke yi ba gafarar Allah suke nema ba; bakunansu ne kawai suke furta abin da babu shi a zukatansu, domin da a ce da gaske suke da sai su tuba daga laifukansu, su gyara halayensu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya faɗa musu cewa, babu mai iya amfana musu komai a wurin Allah idan har Allah ya yi nufin su da alheri ko ya yi nufin su da sharri, watau dai su saduda su mayar da komai wurin Allah, su faɗi gaskiyar al’amari yadda yake, domin kuwa shi Allah masanin komai ne babu wani aikinsu da za su iya ɓoye masa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana gaskiyar abin da ya hana su su bi Manzonsa zuwa Makka, watau shi ne sun yi zaton cewa Manzo da sahabbansa duk za su hallaka ne a wannan tafiyar ba za su ƙara komawa Madina zuwa ga iyalansu ba har abada, Shaiɗan kuma ya ƙawata musu wannan mummunan zaton a zukatansu, suka kuma yi wa Allah mummunan zato na cewa ba zai taimaki Annabinsa ba, suka kuwa tabbata mutane halakakku saboda munana zato da suka yi wa Allah da ƙin fita tare da Manzonsa (ﷺ) ba da wani ƙaƙƙarfan uzuri ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda bai yi imani da Allah da Manzonsa ba to kafiri ne, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadar wa kafirai azaba mai raɗaɗi a ranar alƙiyama tana nan tana jiran su.
Sai kuma Allah ya jaddada wa bayinsa cewa shi ne kaɗai mai mulkin sammai da ƙasa, yana sarrafa su da duk abin da ke cikinsu kamar yadda ya ga dama, yana gafarta wa wanda ya ga dama idan ya bi umarninsa ya shigar da shi Aljanna da falalarsa, yana kuma azabta wanda ya ga dama idan ya bijire wa umarninsa da adalcinsa. Allah kuma ya tabbata mai yawan gafarta zunuban bayinsa ne yayin da suka tuba, mai jin ƙansu ne.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Masu raunin imani a cikin al’umma babu abin da ya dame su sai tara abin duniya ta kowace hanya, musamman hanyar da suke ganin babu wata wahala a cikinta.

2. Raunin imani yakan jawo ƙarancin fahimtar umarnin Allah da haninsa.

Suratul Fat’h (15)
سَيَقُولُ ٱلۡمُخَلَّفُونَ إِذَا ٱنطَلَقۡتُمۡ إِلَىٰ مَغَانِمَ لِتَأۡخُذُوهَا ذَرُونَا نَتَّبِعۡكُمۡۖ يُرِيدُونَ أَن يُبَدِّلُواْ كَلَٰمَ ٱللَّهِۚ قُل لَّن تَتَّبِعُونَا كَذَٰلِكُمۡ قَالَ ٱللَّهُ مِن قَبۡلُۖ فَسَيَقُولُونَ بَلۡ تَحۡسُدُونَنَاۚ بَلۡ كَانُواْ لَا يَفۡقَهُونَ إِلَّا قَلِيلٗا ١٥

15. Waɗanda suka ƙi fita tare da kai za su ce, lokacin da kuka tafi zuwa wasu wuraren ganima don ku samo ta: “Ku bar mu mu bi ku”, suna nufin su musanya zancen Allah ne. Ka ce: “Ba za ku bi mu ba, da ma tuni

haka Allah Ya faɗa.” To za su ce: “A’a, kuna yi mana hassada ne kawai.” Ba haka ba ne, sun kasance ba sa fahimta ne sai ‘yan kaɗan.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana rashin gaskiyar waɗanda suka noƙe suka ƙi fita tare da Manzonsa zuwa Makka, har suka ba da hanzari da cewa za su tsaya don su kula da dukiyoyinsu da ‘ya’yansu. To amma kuma yayin da suka ji cewa Manzon Allah (ﷺ) da muminai za su tafi Khaibar kuma za su samo ganima a can, sai suka fara nuna kwaɗayinsu da haɗamarsu a fili, suka riƙa roƙon Annabi (ﷺ) da sahabbansa cewa, a bar su su fita tare da su don su ma su sami ganima a bulus, wai suna ganin za su iya canza maganar Allah da ya riga ya yi ta cewa, wannan ganimar ta Khaibara ta muminai ce waɗanda suka halarci sulhun Hudaibiyya, su ne kawai Allah ya yi wa alƙawarin wannan ganimar. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya faɗa musu cewa, ba za su bari su bi su ba, domin alƙawarin da ya yi wa mutanen Hudaibiyya na samun wannan ganimar. To amma sai suka riƙa cewa, ai hassada ce kawai ta sa aka hana su fita zuwa Khaibara wai ba umarni ne daga Allah ba. Sai Allah ya mayar musu da martani cewa, ba haka ba ne ba, su ne dai ba sa son bin umarnin Allah da haninsa, don haka ne suka auka cikin saƀonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Waɗanda ba su fita zuwa Makka tare da Manzon Allah (ﷺ) ba Allah ya kwantar musu da hankalinsu, don ya nuna musu cewa, hana su fita zuwa yaƙin Khaibar tare da Musulmi, ba ya faru ne saboda sun fita daga Musulunci ba; an yi musu haka ne saboda wata hikima ta shari’a wadda ta danganci haɗa komai da sababinsa, don haka wannan wata dama ce Allah ya ba su don su fita su nuna gaskiyar imaninsu da biyayyarsu ga Allah da Manzonsa (ﷺ).

2. Aya ta 16 an tabbatar da mu’ujiza ta Alƙur’ani, yayin da yake ba da labaran abubuwan da ba su faru ba sai daga baya kuma suka faru, domin a nan ya yi nuni zuwa ga manya-manyan yaƙe-yaƙe da Musulmi za su yi da manyan ƙasashe ko wasu al’ummu masu tsananin ƙarfin yaƙi, kamar Farisawa da Rumawa waɗanda Musulmi suka yaƙe su a zamanin halifofin Manzon Allah (ﷺ).

3. Samun arziki dukkansa yana cikin biyayya ga Allah da Manzonsa. Dukkan taƀewa kuma tana tare da saƀa musu.

4. An gina hukunce-hukuncen shari’ar Musulunci ne a kan sauƙaƙawa.

Suratul Fat’h (16-17)

قُل لِّلۡمُخَلَّفِينَ مِنَ ٱلۡأَعۡرَابِ سَتُدۡعَوۡنَ إِلَىٰ قَوۡمٍ أُوْلِي بَأۡسٖ شَدِيدٖ تُقَٰتِلُونَهُمۡ أَوۡ يُسۡلِمُونَۖ فَإِن تُطِيعُواْ يُؤۡتِكُمُ ٱللَّهُ أَجۡرًا حَسَنٗاۖ وَإِن تَتَوَلَّوۡاْ كَمَا تَوَلَّيۡتُم مِّن قَبۡلُ يُعَذِّبۡكُمۡ عَذَابًا أَلِيمٗا ١٦ لَّيۡسَ عَلَى ٱلۡأَعۡمَىٰ حَرَجٞ وَلَا عَلَى ٱلۡأَعۡرَجِ حَرَجٞ وَلَا عَلَى ٱلۡمَرِيضِ حَرَجٞۗ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ يُدۡخِلۡهُ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَمَن يَتَوَلَّ يُعَذِّبۡهُ عَذَابًا أَلِيمٗا ١٧

16. Ka ce da waɗanda suka ƙi fita tare da kai daga mutanen ƙauye: “Ba da daɗewa ba za a kirawo ku zuwa wurin wasu mutane masu tsananin yaƙi don ku yaƙe su ko su musulunta. To idan kuka bi (wannan umarni), Allah zai ba ku lada kyakkyawa, idan kuwa kuka ba da baya kamar yadda kuka ba da baya a da can, zai azabtar da ku azaba mai raɗaɗi.”

17. Babu wani laifi a kan makaho, babu kuma wani laifi a kan gurgu, kuma babu wani laifi a kan marar lafiya (game da rashin fita yaƙi). Wanda kuwa ya bi Allah da Manzonsa to zai shigar da shi gidajen Aljanna

waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, wanda kuma ya ba da baya to zai azabtar da shi azaba mai raɗaɗi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya jarraba waɗannan Larabawan ƙauyuka da suka ƙi fita zuwa Makka tare da shi ya sanar da su cewa za a kirawo su don a tura su su yaƙi wasu mutane masu tsananin ƙarfi na yaƙi, su yaƙe su don Allah, ko kuma su shiga Musulunci ba tare da yaƙi ba. To idan sun bi umarnin Allah sun amsa kiransa na fita wannan yaƙin, to sun tabbata masu gaskiya, kuma zai ba su lada kyakkyawa, watau gidan Aljanna; amma idan suka bijire wa yi masa biyayya kamar yadda suka yi a can baya, suka ƙi fita zuwa Makka tare da shi, to zai azabtar da su azaba mai raɗaɗi.
Daga nan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mutanen da aka ba wa damar su zauna a gida ba sai sun fita yaƙi ba saboda suna da uzuri karɓaɓɓe. Waɗannan su ne makafi da guragu da marasa lafiya, su kam babu laifi a kansu idan ba su fita zuwa yaƙi ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, duk wanda ya bi Allah, ya kuma bi Manzonsa, to zai shigar da shi gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, wanda kuwa ya bijire wa Allah da Manzonsa, to zai azabtar da shi azaba mai raɗaɗi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar sahabban Manzon Allah (ﷺ) waɗanda suka yi masa mubaya'a a ranar Hudaibiyya. Allah ya tabbatar musu da cewa ya yarda da su, ya kuma tsarkake zukatansu ya cika su da nutsuwa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gaggauto musu da kyakkyawan sakamako tun a nan duniya kafin ya ba su na lahira idan sun je.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halatta wa wannan al'umma cin ganima, alhalin bai halatta wa waɗanda suka gabace su ba.

Suratul Fat'h (18-19)
*لَّقَدۡ رَضِيَ ٱللَّهُ عَنِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ إِذۡ يُبَايِعُونَكَ تَحۡتَ ٱلشَّجَرَةِ فَعَلِمَ مَا فِي قُلُوبِهِمۡ فَأَنزَلَ ٱلسَّكِينَةَ عَلَيۡهِمۡ وَأَثَٰبَهُمۡ فَتۡحًا قَرِيبٗا ١٨ وَمَغَانِمَ كَثِيرَةٗ يَأۡخُذُونَهَاۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمٗا ١٩

18. Haƙiƙa Allah Ya yarda da muminai yayin da suke yi maka mubaya'a a ƙarƙashin bishiyar nan, to Allah Ya san abin da yake cikin zukatansu, sai Ya saukar musu da nutsuwa Ya kuma saka musu da buɗi na kurkusa.

19. Da kuma ganimomi masu yawa da za su yi ta kwasar su. Allah kuwa Ya kasance Mabuwayi ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falalar da ya yi wa sahabban Manzonsa (ﷺ), watau ya yarda da su lokacin da suke yi wa Manzonsa (ﷺ) mubaya'a a Hudaibiyya a ƙarƙashin bishiya a kan za su jajirce wajen yaƙi tare da shi har su yi nasara ko kuma su yi mutuwar shahada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya san abin da yake cikin zukatansu na imani da ikhlasi da gaskiya, don haka sai ya saukar musu da nutsuwa a zukatansu, ya kuma yi musu sakayya da wani buɗi na kurkusa, watau buɗe Khaibara a madadin rashin samun shiga garin Makka su yi umara.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu tagomashin ganimomi masu yawa da za su samu daga Yahudawan Khaibara, domin Allah ya kasance mabuwayi ne babu mai iya rinjayar sa, mai hikima ne cikin halittarsa da ƙaddararsa da tsarinsa.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Mun kasance mu dubu da ɗari huɗu a ranar Hudaibiyya, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce mana: “Ku ne mafi alherin mutane a bayan ƙasa.” [Bukhari #4154].

An karɓo daga Ma’aƙil ɗan Yasar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Na gan ni a ranar Mubaya’ar ƙarƙashin bishiya, Annabi (ﷺ) yana karɓar mubaya’a daga mutane, ni kuma ina ɗage masa reshenta daga kansa, yawanmu kuwa mutum dubu da ɗari huɗu ne, ba mu yi masa mubaya’a a kan mutuwa ba, mun dai yi masa mubaya’a ne a kan ba za mu gudu ba.” [Muslim #1858].An karɓo daga Salamatu ɗan Akwa’u (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Na yi wa Manzon Allah (ﷺ) mubaya’a a ƙarƙashin bishiya.” Sai aka ce masa: “A kan mene ne kuka yi masa mubaya’a a wannan ranar?” Sai ya ce: “A kan mutuwa.” [Bukhari #4169].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gaskiyar alƙawarin Allah ga muminai da tabbatar musu da abin da ya yi musu alƙawarinsa na ganimomi a lokacin rayuwar Manzon Allah (ﷺ) da ma bayan wafatinsa.

2. Karramawar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa sahabban Manzon Allah (ﷺ) ya kare su daga sharrin Yahudawa, bai ba su damar kai hare-hare a kan iyalan sahabbai ba a Madina yayin da suka yi tafiya zuwa Makka tare da Manzon Allah (ﷺ).

3. Nasarar masu gaskiya a kan maɓarnata sunna ce ta Allah tabbatacciya.

Suratul Fat’h (20-24)
وَعَدَكُمُ ٱللَّهُ مَغَانِمَ كَثِيرَةً تَأۡخُذُونَهَا فَعَجَّلَ لَكُمۡ هَٰذِهِۦ وَكَفَّ أَيۡدِيَ ٱلنَّاسِ عَنكُمۡ وَلِتَكُونَ ءَايَةً لِّلۡمُؤۡمِنِينَ وَيَهۡدِيَكُمۡ صِرَٰطٗا مُّسۡتَقِيمٗا ٢٠ وَأُخۡرَىٰ لَمۡ تَقۡدِرُواْ عَلَيۡهَا قَدۡ أَحَاطَ ٱللَّهُ بِهَاۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٗا ٢١ وَلَوۡ قَٰتَلَكُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوَلَّوُاْ ٱلۡأَدۡبَٰرَ ثُمَّ لَا يَجِدُونَ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ٢٢ سُنَّةَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلُۖ وَلَن تَجِدَ لِسُنَّةِ ٱللَّهِ تَبۡدِيلٗا ٢٣ وَهُوَ ٱلَّذِي كَفَّ أَيۡدِيَهُمۡ عَنكُمۡ وَأَيۡدِيَكُمۡ عَنۢهُم بِبَطۡنِ مَكَّةَ مِنۢ بَعۡدِ أَنۡ أَظۡفَرَكُمۡ عَلَيۡهِمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٗا ٢٤

20. Allah kuma Ya yi muku alƙawarin wasu ganimomi masu yawa da za ku yi ta kwasar su, sai Ya gaggauto muku da wannan (ganimar Khaibara) Ya kuma kame muku hannayen mutanen (wato Yahudu), don kuwa (wannan) ya zama aya ga muminai, Ya kuma shiryar da su hanya madaidaiciya.

21. Ɗaya (ganimar) kuwa ba ku sami iko a kanta ba, haƙiƙa Allah Ya san da ita, Allah kuwa Ya kasance Mai iko ne a kan komai.

22. Da kuwa waɗanda suka kafirta za su yaƙe ku, tabbas da sun juya da baya, sannan ba za su sami wani majiɓinci ko mataimaki ba.

23. (Wannan ita ce) sunnar Allah wadda ta riga ta gabata tun tuni; ba kuwa za ka taɓa samun canji ba game da sunnar Allah.

24. Shi ne kuma Wanda Ya kame muku hannayensu, kuma (Ya kame) musu hannayenku a cikin Makka bayan kuwa Ya riga ya ba ku nasara a kansu. Allah kuma Ya zamanto Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake yi wa muminai albishir na ba su ganimomi masu yawa waɗanda za su samu a yaƙe-yaƙensu na Musulunci waɗanda za su yi a nan gaba, ya kuma gaggauto musu da ganimar Khaibara, ya kuma kame musu hannayen Yahudawa yayin da suka yi niyyar su cutar da iyalansu a bayansu. Sannan kuma don wannan ganimar da aka gaggauto musu da ita ta zama alama ce a gare su da ke nuna taimakon Allah da ƙarfafawarsa a gare su, ya kuma shiryar da su tafarkinsa madaidaici wanda babu karkata a cikinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sake yi musu wani alƙawarin na ba su wasu ganimomi a nan gaba waɗanda a yanzu ba su da ikon samun su, to amma Allah ya tsare musu su bai ba wa wasu iko a kansu ba, har zuwa lokacin da ya ba su iko suka cinye su da yaƙi, kamar Farisawa da Rumawa waɗanda Allah ya ba wa Musulmi ikon cin su da yaƙi bayan a da can ba za su iya tunkarar su da yaƙi ba saboda rauninsu da tsananin ƙarfin waɗannan ƙasashe. Allah kuwa mai iko ne a kan komai babu abin da zai gagare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara wa muminai ƙarfin gwiwa inda ya tabbatar musu da cewa, da kafirai za su yaƙe su, to ba za su iya samun nasara a kansu ba, sai dai su juya da baya su gudu, sannan ba za su sami wani wanda zai jiɓinci al'amarinsu ba, ba kuma za su sami wanda zai taimaka musu ba su yaƙi Musulmi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, wannan ita ce sunnarsa tabbatacciya a kowane zamani a kuma kowane wuri, kuma ita ce sunnarsa da ta riga ta gabata a cikin al'ummun da suka shuɗe kuma babu wani canji game da sunnar Allah.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tuna musu wata ni'imar da ya yi musu lokacin da ya kame musu hannayen mutanen Makka, yayin da mayaƙa mutum tamanin suka nufo su a Hudaibiyya da niyyar cutar da su, to amma Musulmi suka farga suka kuma sami nasarar cafke su gaba ɗayansu a hannu, to amma sai Allah ya kame hannayen muminai ba su kashe su ba, ba su kuma cutar da su ba, sai ma dai suka sake su gaba ɗayansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kasance masanin abin da suke aikatawa ne, don haka yana yi wa bayinsa muminai kyakkyawan tsari a cikin dukan al'amuransu.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "A ranar Hudaibiyya wasu mazaje su tamanin daga cikin mutanen Makka masu ɗauke da makamai suka fito daga ɓangaren dutsen Tan'im suka auka wa Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa suna son su mamaye su, sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi addu'a a kansu, sai aka cafke su, amma daga baya Annabi (ﷺ) ya yi musu afuwa, sai wannan ayar ta 24 ta sauka." [Muslim #1808 da Ahmad #12227].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hana mutane bin hanyar Allah babban laifi ne wanda mai aikata shi ya cancanci azaba mai tsanani daga Allah.

2. Shirin Allah ga bayinsa domin maslahohinsu ya shallake duk wani iliminsu.

3. Gargaɗi a kan canza alaƙa ta addini da kishi na ƙabilanci ko na jini; yin haka aiki ne na mutanen jahiliyya.

4. Kalmar Shahada, watau '*La Ilaha Illal Lahu*' kalma ce ta taƙawa; yin imani da ita da rungumar abin da take koyarwa, kariya ce daga faɗawa cikin azabar Allah.

Suratul Fat'h (25-26)

هُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّوكُمْ عَنِ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ وَٱلْهَدْىَ مَعْكُوفًا أَن يَبْلُغَ مَحِلَّهُۥ ۚ وَلَوْلَا رِجَالٌ مُّؤْمِنُونَ وَنِسَآءٌ مُّؤْمِنَٰتٌ لَّمْ تَعْلَمُوهُمْ أَن تَطَـُٔوهُمْ فَتُصِيبَكُم مِّنْهُم مَّعَرَّةٌۢ بِغَيْرِ عِلْمٍ ۖ لِّيُدْخِلَ ٱللَّهُ فِى رَحْمَتِهِۦ مَن يَشَآءُ ۚ لَوْ تَزَيَّلُواْ لَعَذَّبْنَا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنْهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿٢٥﴾ إِذْ جَعَلَ

ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي قُلُوبِهِمُ ٱلۡحَمِيَّةَ حَمِيَّةَ ٱلۡجَٰهِلِيَّةِ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَعَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَأَلۡزَمَهُمۡ كَلِمَةَ ٱلتَّقۡوَىٰ وَكَانُوٓاْ أَحَقَّ بِهَا وَأَهۡلَهَاۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمَۢا ٢٦

25. Su ne waɗanda suka kafirta suka kuma hana ku isa ga Masallaci mai alfarma, suka kuma hana dabbobin hadaya isa wurin yankansu. Kuma ba don wasu mazaje muminai da wasu mataye muminai da ba ku san su ba, don kada ku kashe su, sannan wani laifi nasu ya same ku ba tare da sani ba, (da Ya ba ku damar yaƙar su. Wannan ya faru ne) don Allah Ya shigar da wanda Ya ga dama cikin rahamarsa. Da sun ware to lalle da Mun azabtar da waɗanda suka kafirta daga cikinsu azaba mai tsanani.

26. Yayin da waɗanda suka kafirta suka sanya kishi irin kishin jahiliyya a cikin zukatansu, sai Allah Ya saukar da nutsuwarsa ga Manzonsa da muminai, Ya kuma kimsa musu kalmar imani, da ma kuma su suka fi cancantarta, kuma (su ne) masu ita. Allah kuma Ya kasance Masanin komai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu dalilai da suka ba wa muminai damar su yaƙi mushirikan Makka, watau saboda sun hana Manzon Allah da muminai su isa zuwa ga Ɗaki mai alfarma na Makka wanda suka baro Madina domin ziyartar sa da yin ibada a wajensa, suka kuma hana hadaya ta isa wurin yankanta, na haramin Makka.
Waɗannan duka dalilai ne da suka ba wa Musulmi damar su auka musu da yaƙi. To abin da kawai ya hana faruwar haka shi ne wasu muminai maza da mata da suke a tsakiyar mushirikan Makka waɗanda ba a ware suke a wani keɓabɓen wuri ko unguwa ba, ga shi kuma su Musulmi ba sanin su suka yi ba, don haka idan suka auka wa kafiran Makka da yaƙi za su iya kashe waɗannan muminan ba tare da sun sani ba, wannan kuwa zai jawo musu faɗawa cikin laifin kisan mumini da kuma biyan diyyoyinsu. To ba don wannan dalili ba da Allah ya ba wa muminai izinin yaƙi don buɗe garin Makka, domin Allah ya shigar da wanda ya ga dama cikin rahamarsa. Saboda haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, da kafirai sun ware gefe ɗaya ba su gauraya da muminai ba, da tabbas ya saukar musu azaba mai tsanani.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a lokacin da aka zo yin *Sulhul Hudaibiyya* kafirai sun sanya kishi a zukatansu irin kishin jahiliyya wanda ba ya da wata alaƙa da tabbatar da gaskiya sai dai son zuciya kawai. Domin a lokacin da za a rubuta takardar yarjejeniya sai suka ƙi yarda a rubuta '*Bismillahir Rahmanir Rahimi*' a farkonta, suka kuma kafe ba za a rubuta wa Manzon Allah siffarsa ta manzanci ba, sai dai kawai a rubuta sunansa zalla, suka kuma kafe a kan cewa Manzon Allah da Musulmi ba za su shiga Makka a wannan shekarar ba sai shekara mai zuwa, wai suna ganin in sun bari ya shiga za su yi abin kunya a wurin sauran 'yan'uwansu Larabawa, domin wai za a riƙa cewa Musulmi sun fi ƙarfinsu ne, shi ya sa har suka sami shiga Makka suka yi umara. To duk da waɗannan abubuwa na ban haushi da renin wayo, Allah ya saukar da nutsuwarsa ga Manzonsa da muminai, bai bari fushi ya sanya sun aikata abin da zai haddasa tashin hankali da hatsaniya ba, har ya kai ga hana tabbatar wannan sulhu, don haka suka danne zukatansu, Allah kuma ya kimsa musu kalmar taƙawa, watau Kalmar Shahada, suka tsaya a kan kiyaye haƙƙoƙinta; da ma kuma su suka fi cancanta da ita, kuma su ne masu ita, domin Allah ya san alherin da ke cikin zukatansu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbata masanin komai ne babu abin da zai ɓoyu gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mafarkin annabawa gaskiya ne.

2. Mu'ujizar Manzon Allah (ﷺ) da karramawar Allah gare shi.

3. Karamcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa muminai, domin yakan ba su abin da zai faranta musu idan suka yi haƙuri game da abin da suka rasa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai cikakken ilimi, ya san lokacin da abu yakan fi zama maslaha ga bawansa, don haka yakan jinkirta bayar da shi gare shi.

Suratul Fat'h (27-28)

لَّقَدۡ صَدَقَ ٱللَّهُ رَسُولَهُ ٱلرُّءۡيَا بِٱلۡحَقِّۖ لَتَدۡخُلُنَّ ٱلۡمَسۡجِدَ ٱلۡحَرَامَ إِن شَآءَ ٱللَّهُ ءَامِنِينَ مُحَلِّقِينَ رُءُوسَكُمۡ وَمُقَصِّرِينَ لَا تَخَافُونَۖ فَعَلِمَ مَا لَمۡ تَعۡلَمُواْ فَجَعَلَ مِن دُونِ ذَٰلِكَ فَتۡحًا قَرِيبًا ٢٧ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَرۡسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلۡهُدَىٰ وَدِينِ ٱلۡحَقِّ لِيُظۡهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدٗا ٢٨

27. Haƙiƙa Allah Ya tabbatar wa Manzonsa gaskiyar mafarkin cewa, lalle za ku shiga Masallaci mai alfarma insha Allahu, kuna cikin aminci kuna masu aske kawunanku da masu yin saisaye, ba tare da kuna jin tsoron (komai) ba, to Ya san abin da ba ku sani ba, sai Ya sanya buɗi na kusa kafin wannan.

28. Shi ne Wanda Ya aiko Manzonsa da shiriya da kuma addini na gaskiya don Ya ɗora shi a kan kowane addini. Allah kuma Ya isa Mai shaida.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) gaskiyar mafarkin da ya yi a Madina, inda ya gan shi tare da sahabbansa sun shiga garin Makka lafiya lau ba tare da suna cikin tsoron kowa ba, har ma sun gama umararsu, wasu sun aske kawunansu gaba ɗaya, wasu kuma sun yi saisaye. Annabi (ﷺ) ya ba wa sahabbansa labarin wannan mafarki nasa suka kuma yi farin ciki sosai. To lokacin da kafirai suka hana su shiga Makka har daga ƙarshe aka yi sulhu a kan cewa, su koma Madina sai shekara mai zuwa su dawo, wannan ya ɓata wa sahabbai rai matuƙa, suka kuma riƙa tambaya game da mafarkin da Manzon Allah (ﷺ) ya yi; to sai kuma ga yadda al'amarin ya kasance. Annabi (ﷺ) ya bayyana musu cewa ai bai faɗa musu cewa a wannan shekarar ne abin zai tabbata ba, don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da gaskiyar mafarkin Manzonsa (ﷺ), musamman ya yi musu tagomashi da gaggauto musu wani buɗi, watau abin da ya gudana na sulhun Hudaibiyya da abin da ya biyo bayansa na buɗe Khaibara, ta hannun muminai waɗanda suka halarci sulhun Hudaibiyya.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jaddada musu matsayin addinin Musulunci, da cewa nasa ne, shi ne wanda ya aiko Manzonsa (ﷺ) da shiriya, watau ilimi mai amfani, da kuma addini na gaskiya, watau aiki nagari, domin ya ɗora shi a kan dukkan addinai gaba ɗaya, kuma Allah ya yi shaida a kan haka, Allah kuwa ya isa mai shaida.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ).

2. Martabar sahabbai da falalarsu a wurin Allah.

3. Tabbatar da tsananinsu ga kafirai masu yaƙar su da tausayin junansu.

4. Tabbatar da yawan ibadarsu wadda suke yi don neman yardar Allah ba wani abu na duniya ba.

5. Tabbatar da cewa, littafin Attaura da Allah ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Linjila da Allah ya saukar wa Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) duka sun zo da bayanin kyawawan siffofin sahabban Annabi (ﷺ).

6. Taimakon juna da haɗin kai suna daga cikin kyawawan halayen sahabban Manzon Allah (ﷺ).

7. Duk mai ƙin sahabban Manzon Allah (ﷺ) ana jiye masa tsoron faɗawa cikin kafirci.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa sahabban Manzon Allah (ﷺ) alƙawarin gafara daga gare shi da kuma gidan Aljanna.

Suratul Fat'h (29)

مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْۖ تَرَىٰهُمْ رُكَّعًا سُجَّدًا يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنًاۖ سِيمَاهُمْ فِى وُجُوهِهِم مِّنْ أَثَرِ ٱلسُّجُودِۚ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمْ فِى ٱلتَّوْرَىٰةِۚ وَمَثَلُهُمْ فِى ٱلْإِنجِيلِ كَزَرْعٍ أَخْرَجَ شَطْـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسْتَغْلَظَ فَٱسْتَوَىٰ عَلَىٰ سُوقِهِۦ يُعْجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلْكُفَّارَۗ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنْهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا ﴿٢٩﴾

29. Muhammadu Manzon Allah ne. Waɗanda kuma suke tare da shi masu tsanani ne a kan kafirai, kuma masu tausayin junansu ne; za ka gan su suna ruku'i suna sujjada suna neman falala daga Allah da yardarsa; alamominsu na gurbin sujjada suna bayyana a fuskokinsu. Wannan shi ne misalinsu a cikin Attaura. Misalinsu kuwa a cikin Linjila kamar shuka ce da ta fitar da reshenta sai ya ƙarfafe ta, sannan ta yi kauri sai ta daidaita a kan tushiyarta ta riƙa ƙayatar da manoma, don Ya cusa wa kafirai haushi. Allah Ya yi wa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari daga cikinsu alƙawarin gafara da lada mai girma.

A wannan ayar ta ƙarshen Sura Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ), babu mai jayayya a kan haka sai kafirai.Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kyawawan siffofin sahabban Manzonsa (ﷺ), waɗanda suka yi hijira da mutanen Madina, ya ambace su kamar haka:
Na ɗaya, su masu tsananta wa kafirai abokan gaba ne ba sa sassauta musu, amma a junansu masu tausaya wa juna ne.
Na biyu, su mutane ne a koyaushe masu tsayar da salloli na farilla da na nafila tare da ikhlasi.
Na uku, su masu neman falala ne daga Ubangijinsu da lada da kuma yardarsa.
Na huɗu, a fuskokinsu suna da alamomi na hasken sujjada da yawan salla. Waɗannan siffofi nasu kuma haka aka bayyana su a cikin Attaura.
Na biyar, wata siffa kuma da aka siffanta su da ita a littafin Linjila ita ce dangane da taimakon junansu da cewa sun yi kama da shuka wadda take fitar da reshenta sai ya ƙarfafe ta sai ta yi kauri ta kuma daidaita a kan tushiyarta, sai cikarta da ƙarfinta su riƙa ba wa manoma sha'awa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafi sahabbai da irin wannan siffa suna taimaka wa junansu wajen ɗaukaka addinin Musulunci da yaɗa da'awarsa, domin ya daɗa cusa haushi a zukatan kafirai, don ganin ci gaban addinin Allah da yaɗuwarsa a ko'ina.
Sai kuma a ƙarshe Allah ya yi wa sahabbai waɗanda suka yi imani da shi da Manzonsa suka yi kyawawan ayyuka alƙawarin samun gafarar zunubansu da kuma samun lada mai girma, watau gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramun ne mumini ya yi gaban kansa cikin wani al'amari na addini ko na rayuwa ba tare da sanin hukuncin Allah da Manzonsa (ﷺ) a kai ba.

2. Dukkan wani al'amari na addini ko na rayuwa mai dangantaka da aiki ko magana ko ƙuduri wanda ya saba wa koyarwar Allah da Manzonsa (ﷺ), wucewa ne gaban Allah da Manzonsa. Duk bidi'o'i a addini za

su shiga ƙarƙashin wannan ayar. Hakanan duk dokokin tsara rayuwa waɗanda suka ci karo da na Allah da Manzonsa, su ma sun shiga ƙarƙashin wannan ayar.

3. Haƙiƙanin imani da taƙawa shi ne bin Manzon Allah (ﷺ) sau da ƙafa da ƙanƙame sunnarsa.

4. Wajabcin yin ladabi ga Manzon Allah (ﷺ) yayin magana da shi ko sauraron maganarsa ko karanta hadisansa ko lokacin ziyarar masallacinsa na Madina, da haramcin kiran sa da sunansa zalla ba tare da wani laƙabi na girmamawa ba, kamar 'ya Manzon Allah' ko 'ya Annabin Allah'. Nuna rashin ladabi gare shi yakan jawo rushewar ladan ayyukan bawa ba tare da ya sani ba.

5. Akwai wasu laifuka waɗanda aikata su yakan iya jawo rushewar ladan aikin Musulmi.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan jarrabi zukatan bayinsa da wasu musibu ta hanyar umarni da hani, to duk wanda ya bi umarnin Allah ya nemi yardarsa ya kauce wa bin son zuciyarsa, to wannan ya cancanci samun taƙawa a zuciyarsa, wanda kuwa ya saɓa wa haka to wannan bai cancanci siffar taƙawa ba.

49-Suratul Hujurat

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna '*Suratul Hujurat*' a dukkan masahifu da littattafan tafsiri da na sunna. Ba ta da wani suna sai wannan. An ba ta wannan sunan ne saboda an ambaci lafazin '*Al-hujurat'* a cikinta a aya ta 4

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya* a wurin dukkan malaman tafsiri.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ɗari da takwas (108) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Mujadala*' kafin '*Suratut Tahrim'*, ta sauka a shekara ta tara bayan hijira.

4. Adadin ayoyinta:
Adadin ayoyinta goma sha takwas ne (18) babu wani saɓani.

5. Dalilin Saukarta:
An karɓo daga Abdullahi ɗan Zubair (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Wani ayari na ƙabilar Banu Tamim sun zo wajen Manzon Allah (ﷺ) suka buƙaci ya naɗa musu shugaba daga cikinsu, sai Abubakar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Ya Manzon Allah, ka naɗa musu Al-Ka'aƙa'u ɗan Ma'abad." Sai shi kuma Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "A'a, ka naɗa musu Al-Aƙra'u ɗan Habis." Sai Abubakar (Allah ya kara masa yarda) ya ce wa Umar: "Manufarka kawai ita ce ka saɓa wa maganata." Sai Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Ni ban yi niyyar saɓa maka ba." Sai suka shiga jayayya, har suka ɗaga muryoyinsu a gaban Manzon Allah (ﷺ), sai wannan ayar ta sauka, watau faɗar Allah: "Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku wuce gaban Allah da Manzonsa...." har zuwa ƙarshen ayar." [Bukhari #4367].

6. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne koya wa al'ummar Musulmi kyawawan halaye da gargaɗin su game da aikata munanan ɗabi'u.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Koyar da Musulmi yadda za su yi wa Manzon Allah (ﷺ) ladabi wajen mu'amala da shi da magana da shi da kuma kiran sa.
• Wajabcin Musulmi su riƙa ba da labarin gaskiya da tantance labari idan ya zo musu, domin yin haka ɗabi'a ce ta muminai.
• Yin sulhu na adalci tsakanin ɓangarorin Musulmi masu faɗa da juna, domin yin haka shi ne 'yan'uwantaka ta gaskiya.
• Kyautata mu'amala tsakanin Musulmi a ɓoye ko a sarari da kauce wa duk wata mummunar ɗabi'a da za ta haddasa gaba da ƙiyayya a tsakaninsu.

• Gyara wasu munanan ɗabi’u na wasu mutanen ƙauye waɗanda ba su daɗe da barin kafirci ba.

Suratul Hujurat (1-3)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيِ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ١ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَرۡفَعُوٓاْ أَصۡوَٰتَكُمۡ فَوۡقَ صَوۡتِ ٱلنَّبِيِّ وَلَا تَجۡهَرُواْ لَهُۥ بِٱلۡقَوۡلِ كَجَهۡرِ بَعۡضِكُمۡ لِبَعۡضٍ أَن تَحۡبَطَ أَعۡمَـٰلُكُمۡ وَأَنتُمۡ لَا تَشۡعُرُونَ ٢ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَغُضُّونَ أَصۡوَٰتَهُمۡ عِندَ رَسُولِ ٱللَّهِ أُوْلَـٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱمۡتَحَنَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُمۡ لِلتَّقۡوَىٰۚ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٌ عَظِيمٌ ٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku wuce gaban Allah da Manzonsa, kuma ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai ji ne, Masani.

2. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku ɗaga muryoyinku sama da muryar Annabi, kada kuma ku ɗaga masa murya wajen yin magana kamar yadda shashinku yake ɗaga wa shashi, don kada ayyukanku su lalace alhali kuwa ku ba ku sani ba.

3. Lalle waɗanda suke yin ƙasa-ƙasa da muryoyinsu a wurin Manzon Allah, waɗannan su ne waɗanda Allah Ya jarrabi zukatansu da imani. Suna da (sakamakon) gafara da lada mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira muminai waɗanda suka yi imani da shi, suka yarda za su bi dokokin shari’arsa, ya hana su wucewa gaban Allah da Manzonsa (ﷺ) wajen aikata wani aiki ko faɗar wata magana kafin su saurari abin da Allah da Manzonsa za su faɗa.
Duk da cewa wannan ayar ta sauka ne game da jayayyar da ta faru tsakanin Abubakar (Allah ya ƙara masa yarda) da Umar a gaban Manzon Allah (ﷺ) a kan wanda ya cancanta a naɗa shugaba ga ƙabilar Tamim, kafin su ji abin da Manzo (ﷺ) zai faɗa, to amma ayar ta ƙunshi umarni ne ga muminai gaba ɗaya, watau duk wata magana ko wani aiki kada mumini ya sha gaban Allah da Manzonsa da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su kiyaye dokokinsa ta hanyar bin umarninsa da guje wa haninsa, ya tabbatar musu cewa, shi mai jin dukkan maganganunsu ne, kuma masanin dukkan ayyukansu, don haka zai yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake yin kira ga muminai da kada su ɗaga muryoyinsu a kan muryan Annabi (ﷺ) yayin da suke masa magana, kada kuma su riƙa kiran sa da sunansa zalla, kamar yadda suke kiran junansu; su kira shi da siffar manzanci ko annabci da kuma tausasa murya, domin saɓa wa wannan umarni zai iya jawo musu rushewar ladan ayyukansu ba tare da sun ankara ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Zubair (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya kasance, bayan saukar wannan ayar, ba ya iya jiyar da Manzon Allah (ﷺ) sautinsa har sai Manzon Allah ya nemi ƙarin bayani daga gare shi.” [Bukhari #4845].

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Yayin da wannan ayar ta sauka: “Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku wuce gaban Allah da Manzonsa....” har zuwa ƙarshen aya ta 2, to akwai Sabitu ɗan Kaisu ɗan Shammas wani mutum mai babbar murya, sai ya ce: “Ni ne wanda na kasance ina ɗaga muryata ga Manzon Allah (ﷺ), don haka aikina ya rushe, ni ɗan wuta ne.” Sai ya zauna a gidansa cikin iyalansa cike da baƙin ciki. Da Manzon Allah bai gan shi ba kwana biyu, sai ya tambayi labarinsa, daga nan wasu suka je suka same shi suka faɗa masa cewa Manzon Allah (ﷺ) yana tambayar labarinsa, me ya same shi? Sai ya ce: “Ni ne wanda nake ɗaga muryata a kan muryar Annabi (ﷺ), don haka aikina ya lalace, kuma ni yanzu ɗan wuta ne.” Sai suka dawo suka faɗa wa Manzon Allah (ﷺ) labarinsa da abin da ya faɗa

musu, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “A’a, shi ɗan Aljanna ne.” Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Sai muka riƙa ganin sa yana yawo a cikinmu alhalin mun san shi ɗan Aljanna ne. Lokacin yaƙin Al-Yamama (watau yaƙi da masu ridda) sai rundunarmu ta ɗan ja da baya, sai ga Sabi’tu ɗan Kaisu ya zo sanye da likkafaninsa a jikinsa ya sanya turare yana cewa: “Tir da irin abin da kuke saba wa ‘yan’uwanku.” Sai ya yi ta yaƙi har aka kashe shi.” [Ahmad #12399 da Muslim #119].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi waɗanda suke yin ƙasa-ƙasa da muryoyinsu a gaban Manzon Allah (ﷺ) da cewa su ne waɗanda ya jarrabi zukatansu saboda taƙawa gare shi, ya zaɓe su ya ba su ita, ya kuma tabbatar musu da gafarar zunubansu da kuma lada mai girma a ranar alƙiyama, watau ya shigar da su gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin nuna ladabi ga Manzon Allah (ﷺ).

2. Rashin hankali shi yake sanya wasu munana ladabinsu ga waɗanda ya wajaba su girmama, kamar malamansu da iyayensu.

3. Rahamar Allah da falalarsa, yayin da ya bar musu ƙofar tuba a buɗe don su tuba su gyara ayyukansu.

Suratul Hujurat (4-5)
إِنَّ ٱلَّذِينَ يُنَادُونَكَ مِن وَرَآءِ ٱلۡحُجُرَٰتِ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡقِلُونَ ۝٤ وَلَوۡ أَنَّهُمۡ صَبَرُواْ حَتَّىٰ تَخۡرُجَ إِلَيۡهِمۡ لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ۝٥

4. Lalle waɗanda suke kiran ka ta bayan ɗakuna yawancinsu ba su da hankali.

5. Da za su yi haƙuri har sai ka fito wurinsu da ya fiye musu alheri. Allah kuma Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya soki wasu mutanen ƙauye da suke zuwa Madina wurin Manzon Allah (ﷺ) don wata buƙatarsu, sai su samu yana gidansa cikin ɗaya daga ɗakunan matansa, sai su kasa haƙura har sai ya fito, sai su riƙa ƙwala masa kira ta bayan ɗakunan matansa, suna kuma kiran sunansa zalla babu wani ladabi ko girmamawa, sai Allah ya siffanta yawancinsu da cewa ba su da hankali.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, da a ce sun yi haƙuri sun jira har sai ya fito wajensu da ya fi musu alheri, saboda yin haka shi ne girmamawa da nuna ladabi gare shi. Don haka ya ja hankalinsu zuwa ga tuba da neman gafara a kan laifukansu, domin shi mai gafara ne da jin ƙai ga bayinsa masu tuba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin tabbatar da ingancin labari kafin aiki da shi ko yaɗa shi, musamman idan ya fito daga bakin wanda ake tuhumarsa da fasiƙanci.

2. Haɗarin karɓar labari wanda ba a tantance gaskiyarsa ba, domin yakan iya jawo salwartar rayuka da dukiyoyin waɗanda ba su ji ba ba su gani ba, daga ƙarshe a zo ana nadama bayan ɓarna ta riga ta auku.

3. Duk wanda ba a san komai game da shi ba, to ba ya halatta a dogara da labarinsa har sai an tabbatar da nagartarsa.

4. Duk wanda aka tantance gaskiyarsa da nagartarsa, to ana iya karɓar labarinsa, sai ko idan an gano wani kuskure nasa ko giɓi cikin labarinsa.

5. In da a ce shari'a za ta biye wa sahabban Manzon Allah (ﷺ) a cikin yawancin al'amura da suke so, to da sun tsinci kawunansu cikin wahala, to ina kuma ga waɗanda suka zo bayansu waɗanda ba su kama ƙafarsu a nagarta da tsoron Allah ba?

6. Tsananin tausayin Manzon Allah (ﷺ) ga al'ummarsa.

7. Falalar sahabban Annabi (ﷺ) da darajarsu, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya sanya musu son imani ya kuma ƙawata shi a zukatansu, ya sanya musu ƙin kafirci da fasiƙanci da saɓonsa, ya shiryar da su hanya madaidaiciya da falalarsa da ni'imarsa.

Suratul Hujurat (6-8)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن جَآءَكُمۡ فَاسِقُۢ بِنَبَإٖ فَتَبَيَّنُوٓاْ أَن تُصِيبُواْ قَوۡمَۢا بِجَهَٰلَةٖ فَتُصۡبِحُواْ عَلَىٰ مَا فَعَلۡتُمۡ نَٰدِمِينَ ٦ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ فِيكُمۡ رَسُولَ ٱللَّهِۚ لَوۡ يُطِيعُكُمۡ فِي كَثِيرٖ مِّنَ ٱلۡأَمۡرِ لَعَنِتُّمۡ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ حَبَّبَ إِلَيۡكُمُ ٱلۡإِيمَٰنَ وَزَيَّنَهُۥ فِي قُلُوبِكُمۡ وَكَرَّهَ إِلَيۡكُمُ ٱلۡكُفۡرَ وَٱلۡفُسُوقَ وَٱلۡعِصۡيَانَۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلرَّٰشِدُونَ ٧ فَضۡلٗا مِّنَ ٱللَّهِ وَنِعۡمَةٗۚ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٨

6. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan wani fasiƙi ya zo muku da wani labari, to ku yi bincike, don kada ku cuci mutane cikin rashin sani, sannan ku wayi gari kuna masu nadama game da abin da kuka aikata.

7. Kuma ku sani cewa Manzon Allah yana cikinku. Da zai biye muku game da al'amura masu yawa, tabbas da kun wahala, sai dai kuma Allah Ya sa muku son imani Ya kuma ƙawata shi a cikin zukatanku, Ya kuma sa muku ƙin kafirci da fasiƙanci da saɓo. Waɗannan su ne shiryayyu.

8. (Wannan) falala ce daga Allah da kuma ni'ima, Allah kuwa Masani ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya koyar da bayinsa muminai wata kyakkyawar hanya ta karɓar labarin da aka zo musu da shi da cewa, duk sanda wani fasiƙi ya zo musu da wani labari game da wasu mutane, to su tsaya su yi kyakkyawan bincike game da ingancin labarin ko rashin ingancinsa, kada su yi gaggawar gaskata shi don kada su auka wa wasu mutane a bisa rashin sani, su kuma dawo daga baya suna da-na-sani game da abin da suka aikata na cutar da waɗanda ba su ji ba ba su gani ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi sahabban Manzon Allah (ﷺ) inda ya nuna musu cewa, su sani fa Manzon Allah (ﷺ) yana nan cikinsu kuma ana saukar masa da wahayi a kan abubuwan da suke faruwa, don haka su guji yi masa ƙarya, domin duk wanda ya faɗa masa ƙarya, to wahayi zai zo masa ya fallasa shi. Ya kuma tabbatar musu da cewa Manzon Allah (ﷺ) ya fi su sanin abin da zai zame musu maslaha a rayuwarsu da addininsu; da zai biye musu a kan al'amura da dama waɗanda suke nema daga gare shi, to da sun faɗa cikin wahala wadda shi ba zai so ta same su ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falalar da ya yi musu yayin da ya sanya musu son imani ya ƙawata shi a zukatansu don haka suka yi imani, ya kuma sa musu ƙin kafirci da fasiƙanci da saɓon Allah, don haka suka riƙa guje musu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, masu waɗannan siffofi su ne shiryayyu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa siffantuwarsu da son alheri a zukatansu da ƙin sharri wata falala ce da ni'ima Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu, kuma ya san bayinsa masu gode masa, don haka zai ƙara musu, kuma mai hikima ne domin yana ajiye komai a muhallinsa da ya dace.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin yin sulhu na adalci tsakanin Musulmi masu faɗa da junansu.

2. Halaccin yaƙar ɓangaren da ya ƙi yarda da sulhu ya ci gaba da ta'addanci har sai ya dawo ya amince da sulhu.

3. Faruwar yaƙi a tsakanin Musulmi ba ya fitar da su daga Musulunci.

4. Yana daga cikin nagartar imani yin sulhu tsakanin Musulmi masu faɗa da junansu.

5. 'Yan'uwantakar Musulunci ta fi ƙowace 'yan'uwantaka ƙarfi da muhimmanci, don haka duk inda Musulmi yake ɗan'uwan Musulmi ne daga ƙowace ƙabila ya fito kuma ko ɗan wace ƙasa ne.

6. Rashin samar da sulhu a tsakanin Musulmi masu faɗa da juna yana daga manyan abubuwa da za su hana samun rahamar Allah.

Suratul Hujurat (9-10)
وَإِن طَآئِفَتَانِ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٱقۡتَتَلُواْ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَهُمَاۖ فَإِنۢ بَغَتۡ إِحۡدَىٰهُمَا عَلَى ٱلۡأُخۡرَىٰ فَقَٰتِلُواْ ٱلَّتِي تَبۡغِي حَتَّىٰ تَفِيٓءَ إِلَىٰٓ أَمۡرِ ٱللَّهِۚ فَإِن فَآءَتۡ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَهُمَا بِٱلۡعَدۡلِ وَأَقۡسِطُوٓاْۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُقۡسِطِينَ ۝٩ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ إِخۡوَةٞ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَ أَخَوَيۡكُمۡۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ۝١٠

9. Idan kuma wasu ƙungiyoyi biyu na muminai suka yaƙi junansu sai ku yi sulhu a tsakaninsu; to idan ɗayarsu ta yi ta'adda a kan ɗayar, to sai ku yaƙi wadda ta yi ta'addar har sai ta komo zuwa bin umarnin Allah. Idan ta komo sai ku yi sulhu a tsakaninsu bisa adalci, ku kuma yi adalci; lalle Allah Yana son masu adalci.

10. Lalle muminai 'yan'uwan juna ne, sai ku yi sulhu a tsakanin 'yan'uwanku. Kuma ku kiyaye dokokin Allah don a ji ƙan ku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nusantar da muminai yadda za su yi sulhu tsakanin jama'a biyu masu faɗa da juna daga cikinsu, ya umarce su da su yi musu sulhu ta hanyar hukunci da shari'ar Allah a kan abin da suke faɗa game da shi. To amma idan ɗaya jama'ar ta ƙi yarda a yi musu sulhu, ta yi ta'addanci a kan ɗayar, to Allah ya ba wa muminai dama su yaƙi masu ta'addancin har sai sun saduda sun yarda da hukuncin Allah, to idan sun dawo sun yarda a yi musu hukuncin Allah, to muminai sai su yi musu sulhu, ya kuma umarce su da su tabbata sun yi musu adalci, domin lalle Allah yana son masu adalci a cikin hukuncinsu.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ka taimaki ɗan'uwanka yana azzalumi ko wanda aka zalunta." Anas ya ce: "Ya Manzon Allah, wannan zan iya taimakonsa yayin da aka zalunce shi, to yaya zan taimake shi yana azzalumi?" Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ka hana shi yin zalunci, wannan shi ne taimakonka a gare shi." [Bukhari #6952].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An ba wa Annabi (ﷺ) shawarar ya je ya haɗu da Abdullahi ɗan Ubayyu (shugaban munafukan Madina) sai Annabi (ﷺ) ya hau jakinsa ya tafi tare da wasu Musulmi, suka wuce ta wata hanya mai taɓo. Lokacin da Manzon Allah (ﷺ) ya iso wajensa sai ya ce masa: "Tafi ka ba ni wuri, Wallahi warin jakinka ya dame ni." Sai wani mutumin Madina ya ce masa: "Wallahi

tabbas jakin Manzon Allah (ﷺ) ya fi ka ƙamshi." Sai wani mutum ɗan ƙabilar Abdullahi ɗan Ubayyu ya fusata, sai suka shiga zage-zage da wannan mutum, sai ƙabilar kowane daga cikin mutanen nan biyu suka taso a fusace don taimakon ɗan'uwansu, har suka fara doke-doke a tsakaninsu da itatuwan dabino da hannaye da takalma. Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Sai muka samu labari cewa an saukar da wannan ayar ta 9." [Bukhari #2691].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa muminai cewa su 'yan'uwan juna ne waɗanda 'yan'uwantaka ta imani da Musulunci ta haɗa su, don haka ya wajaba su yi sulhu a tsakanin 'yan'uwansu masu rigima da juna, su kuma kiyaye dokokin Allah don su rabauta da rahamarsa.

An karbo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Musulmi ɗan'uwan Musulmi ne, kada ya zalunce shi kada kuma ya sallama shi. Wanda duk ya taimaka ya biya wa ɗan'uwansa buƙatarsa, to shi ma Allah zai biya masa buƙatarsa, duk kuma wanda ya yaye wa Musulmi wata damuwa, to shi ma Allah zai yaye masa damuwarsa ta ranar alƙiyama. Wanda ya rufa wa Musulmi asiri, shi ma Allah zai rufa masa asiri a ranar alƙiyama." [Bukhari #2442 da Muslim #2580].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramun ne wani Musulmi ya yi wa ɗan'uwansa Musulmi ba'a ko izgili, ta yiwu wanda ake yi wa izgilin ya fi mai yi masa izgili alheri, domin ba mai yi wa ɗan'uwansa Musulmi izgili sai in ya siffantu da munanan halaye.

2. An ambaci 'mutane' da 'mata' da sigar jam'i saboda yawanci an fi yin izgili da ba'a ne a bainar jama'a, watau taron na maza ne ko na mata.

3. Haramun ne Musulmi ya aibata ɗan'uwansa Musulmi, domin idan ya yi haka kamar kansa yake aibatawa, saboda Musulmi kamar jiki ɗaya ne duk wanda aka taɓa kamar an taɓa sauran ne.

4. An hana jifan juna da mummunan laƙabi, kamar sunan banza ko na kafirai. Amma kyakkyawan laƙabi bai shiga cikin wannan hani ba, kamar As-Siddiƙ da Al-Faruƙ da sauransu.

Suratul Hujurat (11)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا يَسۡخَرۡ قَوۡمٞ مِّن قَوۡمٍ عَسَىٰٓ أَن يَكُونُواْ خَيۡرٗا مِّنۡهُمۡ وَلَا نِسَآءٞ مِّن نِّسَآءٍ عَسَىٰٓ أَن يَكُنَّ خَيۡرٗا مِّنۡهُنَّۖ وَلَا تَلۡمِزُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَلَا تَنَابَزُواْ بِٱلۡأَلۡقَٰبِۖ بِئۡسَ ٱلِٱسۡمُ ٱلۡفُسُوقُ بَعۡدَ ٱلۡإِيمَٰنِۚ وَمَن لَّمۡ يَتُبۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ١١

11. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada wasu mutane su yi wa wasu mutane izgili, mai yiwuwa ne su zamanto sun fi su alheri, kuma kada wasu mata (su yi wa) wasu mata (izgili), mai yiwuwa ne su zamanto sun fi su alheri; kada kuma ku riƙa aibata junanku, kuma kada ku riƙa jifan juna da munanan laƙuba (da kuke ƙi). Tir da sunan fasiƙanci bayan imani. Wanda duk bai tuba ba, to waɗannan su ne azzalumai.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin muminai a kan yadda ya wajaba su yi mu'amala da junansu, inda ya gargaɗe su a kan cewa kada wasu mutane su yi wa wasu mutane izgili ko ba'a, domin yana yiwuwa waɗanda suke yi wa izgilin su fi su a wurin Allah; hakanan kada wasu mata su riƙa yi wa wasu mata izgili, domin mai yiwuwa ne matan da suke yi wa izgilin su fi su a wurin Allah, saboda babu wanda ya san fifikon da yake tsakanin wani da wani sai shi Allah kaɗai. Sannan ya hana su su riƙa aibata juna, su kuma daina jifan junansu da munanan laƙuba, kamar yadda wasu mutanen Madina suke yi kafin zuwan

Manzon Allah (ﷺ). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya aikata irin wannan to ya zama fasiƙi, kuma tir da siffar fasiƙanci bayan imani. Don haka su gaggauta tuba zuwa ga Allah, wanda kuwa bai tuba ba ya yi watsi da waɗannan ayyuka na saɓon Allah, to yana cikin azzalumai waɗanda suka jefa kansu cikin hallaka.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi game da munana zato ga mumini da tuhumar sa ba tare da ƙwaƙƙwaran dalili ba.

2. Tabbatar da cewa, yawancin zace-zace babu alheri a cikinsu, kuma hanya ce ta faɗawa cikin saɓon Allah.

3. Ana son kyautata wa mumini zato da nema masa hanzari game da abin da zahirinsa ba mai kyau ba ne.

4. Haramcin binciken laifukan mutane don nufin kunyata su da zubar musu da mutunci. Babu laifi ga shugaba wanda alhakin kula da al'umma ya rataya a wuyansa ya binciki masu laifi idan ya samu labarin suna ƙulla ko aikata abin da zai cutar da al'umma ta fuskar addininsu ko lafiyarsu da zamantakewarsu.

5. Haramcin faɗar aibin wani a bayan idonsa ba tare da wata maslaha ba. Amma idan akwai maslaha da ta shafi mutane kamar mai neman shawara game da aure ko wani kasuwanci ko mai bayanin laifin da aka yi masa ga wanda zai bi masa haƙƙinsa, wannan babu laifi a cikinsa.

Suratul Hujurat (12)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱجۡتَنِبُواْ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلظَّنِّ إِنَّ بَعۡضَ ٱلظَّنِّ إِثۡمٞۖ وَ لَا تَجَسَّسُواْ وَلَا يَغۡتَب بَّعۡضُكُم بَعۡضًاۚ أَيُحِبُّ أَحَدُكُمۡ أَن يَأۡكُلَ لَحۡمَ أَخِيهِ مَيۡتٗا فَكَرِهۡتُمُوهُۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ تَوَّابٞ رَّحِيمٞ ١٢

12. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku nisanci yawancin zace-zace, lalle shashin zace-zace laifi ne; kada kuma ku riƙa binciken laifukan wasu, kuma kada shashinku ya riƙa gibar shashi. Yanzu ɗayanku zai so ya ci naman ɗan'uwansa matacce? To sai kuka ƙi shi. To ku kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Mai karɓar tuba ne, Mai jin ƙai.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake kiran muminai da siffarsu ta imani ya hana su aikata wasu miyagun ɗabi'u guda uku:

Na ɗaya, su nisanci yawancin zace-zace marasa tushe ko wani ƙwaƙƙwaran dalili, domin wani zaton laifi ne, kamar munana zato ga wanda a zahirinsa mutumin kirki ne.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ina gargaɗin ku da ku bar zato, domin zato ya fi kowane zance zama ƙarya." [Bukhari #5143, 5144 da Muslim #2563, 2564].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya dubi Ka'aba ya ce: "Maraba da ke Ɗakin Allah, me ya kai girmanki, me ya kai girman alfarmarki, amma lalle mumini ya fi ki alfarma a wurin Allah. Abu ɗaya Allah ya haramta tare da ke, amma abubuwa uku ya haramta tare da mumini: Jininsa da dukiyarsa da yi masa mummunan zato." [Al-Baihaƙi, *Shu'abul Iman* #6280 da Al-AlBani *As-Sahiha* #3420].

Na biyu, su nisance bibiyar laifukan wasu da binciken gano aibinsu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ku guji zato, domin zato shi ne zance mafi zama ƙarya, kada ku yi satar sauraro, kada ku binciki laifukan wasu, kada ku yi wa juna hassada, kada kuma ku ƙi juna, kada ku ba wa juna baya, ku zama bayin Allah ‘yan’uwan juna.” [Bukhari #6064 da Muslim #6563].

An karɓo daga Mu’awiya (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle kai idan ka riƙa binciken laifukan mutane to ka lalata su, ko ka yi kusa ka lalata su.” [Abu Dawud #4888 da Ibn Hibban #5760].

Na uku, su guji yi wa junansu giɓa, watau ɓata mutum a bayan idonsa, har ma saboda muninsa Allah ya siffanta shi da cewa ya yi daidai da mutum ya ci naman ɗan’uwansa bayan ya mutu, wanda kuwa hakan abin ƙyama ne a wurinsa, don haka su ƙyamaci yi da mutane a bayan idonsu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa, mene ne giba? Sai ya ce: “Ka ambaci ɗan’uwanka da abin da yake ƙi?” Sai aka ce masa: “To idan abin da na faɗa game da ɗan’uwana yana da shi fa?” Sai ya ce: “Idan yana da abin da ka faɗa a kansa, to ka yi masa giba, idan kuma ba ya da shi, to ka yi masa ƙage.” [Muslim #2589 da Abu Dawud #4874].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lokacin da aka yi tafiya da ni zuwa sama na wuce ta gaban wasu mutane masu zaƙo-zaƙon farata na tagulla suna kartar fuskokinsu da ƙirazansu, sai na ce: “Su wane ne waɗannan ya Jibrilu?” Sai ya ce: “Waɗannan su ne waɗanda suke cin naman mutane (watau suke gulmar su bayan idonsu) suke auka wa mutuncinsu.” [Ahmad #13340 da Abu Dawud #4878].

Sannan Allah ya umarci muminai da su kiyaye dokokinsa, su aikata abin da ya umarce su, su guji abin da ya hana su, ya kuma tabbatar musu da cewa shi mai karɓar tuban bayinsa ne, mai rahama gare su.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Asalin dukkan ‘yan’adam ɗaya ne, don haka babu dalilin da wani zai riƙa hura wa wani hanci yana yi masa alfahari da asali.

2. Manufar halittar mutane al’ummu da ƙabilu daban-daban shi ne don su san junansu, kowa ya san asalin iyayensa da kakanninsa, domin a riƙa danganta shi da su, ba don fariya ko girman kai ko nuna wariya saboda jinsinsa ko launin fatarsa ba. Wannan shi ne tsarin da Musulunci ya kawo wa ‘yan’adam.

Suratul Hujurat (13)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّا خَلَقۡنَـٰكُم مِّن ذَكَرٖ وَأُنثَىٰ وَجَعَلۡنَـٰكُمۡ شُعُوبٗا وَقَبَآئِلَ لِتَعَارَفُوٓاْۚ إِنَّ أَكۡرَمَكُمۡ عِندَ ٱللَّهِ أَتۡقَىٰكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٞ ١٣

13. Ya ku mutane, lalle Mu Muka halicce ku daga namiji da mace, Muka kuma sanya ku al’ummu da ƙabilu don ku san juna. Lalle mafi girmanku a wurin Allah shi ne wanda ya fi ku taƙawa. Lalle Allah Masanin sarari ne, Masanin ɓoye.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira mutane gaba ɗayansu ya kuma bayyana musu matsayinsu a wurinsa da kuma dangantakarsu da junansu, inda ya tabbatar musu da cewa shi ne ya halicce su daga namiji ɗaya da mace ɗaya, watau Adamu da Hauwa’u, don haka dukkansu asalinsu guda ne,

saboda haka babu dalilin da zai sa wani ya yi wa wani alfahari da asali. Sannan kuma ya nufe su da zama al'ummu daban-daban da ƙabilu masu yawa a wurare daban-daban, don su san junansu, ba don su yi wa juna alfahari ba, domin fifiko ba ya samuwa sai da taƙawa, don haka ya tabbatar musu da cewa mafi girmansu a wurinsa shi ne wanda ya fi taƙawa, watau kiyaye dokokinsa. Sannan ya bayyana cewa, lalle shi masanin halin kowa ne, ya san wanda yake kammalalle da wanda ba kammalalle ba daga cikinku.

An karɓo daga Uƙbatu ɗan Amir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle asalin kowane daga cikinku ba abin aibatawa ba ne, dukkanku 'ya'yan Adamu ne, tsarekun juna ne, babu wanda ya fi wani falala sai da addini da taƙawa. Allah ba zai tambaye ku game da asalinku ko nasabarku a ranar alƙiyama ba, wanda ya fi ku girma a wurin Allah shi ne wanda ya fi taƙawa." [Ahmad #17446].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Annabi (ﷺ) wane ne ya fi girma a cikin mutane? Sai ya ce: "Wanda ya fi su girma a wurin Allah shi ne wanda ya fi su taƙawa...." [Bukhari #3353 da Muslim #2378].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bambanci tsakanin Musulunci da imani. Musulunci shi ne ayyuka na zahiri bayan furta Kalmar Shahada, watau tsayar da salla da azumi da ba da zakka da hajji da sauran wajiban Musulunci. Imani kuwa shi ne gaskatawar zuciya da kawar da duk wani kokwanto bayan gaskatawa da shikashikan imani guda shida, watau imani da Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa da ranar lahira da ƙaddara mai daɗi ko marar daɗi. Don haka imani ya ƙunshi furuci na baka da ƙudurcewa ta zuciya da kuma aiki na gaɓoɓi.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya buƙatar wani ya faɗa masa addininsa, don haka duk wani mai ibada ba a shar'anta masa furta niyya ba yayin da ya zo gabatar da wata ibada, kamar salla ko azumi ko hajji, watau ya ce 'na yi niyyar aikata kaza', domin niyya ita ce 'nufi', watau mutum ya san me ya nufa lokacin ibadarsa.

3. Shiriya zuwa ga Musulunci baiwa ce daga Allah, yana datar da wanda ya ga dama daga cikin bayinsa da shiriyarsa.

4. Sanin gaibu na Allah ne shi kaɗai.

Suratul Hujurat (14-18)

۞قَالَتِ ٱلۡأَعۡرَابُ ءَامَنَّاۖ قُل لَّمۡ تُؤۡمِنُواْ وَلَٰكِن قُولُوٓاْ أَسۡلَمۡنَا وَلَمَّا يَدۡخُلِ ٱلۡإِيمَٰنُ فِي قُلُوبِكُمۡۖ وَإِن تُطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ لَا يَلِتۡكُم مِّنۡ أَعۡمَٰلِكُمۡ شَيۡـٔاۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ١٤ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ لَمۡ يَرۡتَابُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّٰدِقُونَ ١٥ قُلۡ أَتُعَلِّمُونَ ٱللَّهَ بِدِينِكُمۡ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١٦ يَمُنُّونَ عَلَيۡكَ أَنۡ أَسۡلَمُواْۖ قُل لَّا تَمُنُّواْ عَلَيَّ إِسۡلَٰمَكُمۖ بَلِ ٱللَّهُ يَمُنُّ عَلَيۡكُمۡ أَنۡ هَدَىٰكُمۡ لِلۡإِيمَٰنِ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ١٧ إِنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ غَيۡبَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٨

14. (Larabawa) ƙauyawa suka ce: "Mun yi imani." Ka ce: "Ba ku yi imani ba, sai dai ku ce 'mun musulunta', don kuwa imani bai riga ya shiga zukatanku ba; idan kuwa kuka bi Allah da Manzonsa, to ba zai tauye muku wani abu daga (ladan) ayyukanku ba. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai rahama."

15. Muminai kawai su ne waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, sannan ba su yi kokwanto ba, suka kuma yi yaƙi da dukiyoyinsu da rayukansu a hanyar Allah, Waɗannan su ne masu gaskiya.

16. Ka ce: “Yanzu kwa riƙa sanar da Allah addininku, alhali kuwa Allah Yana sane da abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa? Allah kuwa Masanin komai ne.”

17. Suna yi maka gorin sun musulunta; ka ce: “Kada ku yi min gorin musuluntarku; a’a, Allah ne ma zai yi muku gori don Ya shiryar da ku zuwa ga imani, idan kun kasance masu gaskiya.”

18. Lalle Allah Yana sane da abin da yake ɓoye a sammai da ƙasa, Allah kuma Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi na ƙarshen Sura Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayani ne a kan wasu Larabawan ƙauye waɗanda suka shiga addinin Musulunci ba tare da cikakkiyar fahimtarsa ba, ba su kuma tsaya sun yi aiki da abin da imani yakan hukunta ba, to amma duk da wannan sai suka riƙa cika baki suna tinƙaho cewa ai su sun yi imani da Allah da Manzonsa. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya faɗa musu cewa ba su yi imani cikakke ba, don haka su daina kai kansu matsayin da ba su kai ba, su kuma daina cika baki; su dai kawai su ce sun musulunta, watau sun miƙa wuya, su tsaya iya nan, domin kuwa imani bai riga ya ratsa zukatansu ba, amma duk da haka ana sa ran nan gaba imani ya ratsa zukatan nasu, su zama cikakkun muminai. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu abin da za su yi imani ya ratsa su, watau su bi Allah da Manzonsa wajen kyautata imaninsu da ayyukansu da nisantar abubuwan da aka haramta musu. Idan har sun aikata haka, to Allah ba zai rage musu komai daga ladan ayyukansu ba, zai ba su sakamakonsu cikakke. Allah kuma mai gafara ne ga duk wanda ya tuba ya gyara aikinsa, kuma mai rahama ne ga bayinsa.

An karɓo daga Sa’adu ɗan Abu Waƙƙas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wasu jama’a sun zo wurin Annabi (ﷺ), sai ya ba su kyauta ya bar mutum ɗaya bai ba shi ba, sai Sa’ad ya ce: “Ya Manzon Allah, ka ba su kyauta dukkansu ka bar wane ba ka ba shi ba, Wallahi ina ganin sa mumini ne.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ko dai Musulmi.” Ya faɗi haka sau uku. [Bukhari #1478 da Musulmi #150].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana waɗanda suke muminai na gaskiya, waɗanda za su iya buɗa baki su ce su muminai ne, da cewa su ne waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa sannan ba su yi wani kokwanto game da imaninsu ba, suka kuma yi jihadi da dukiyoyinsu da kawunansu don Allah, lalle masu irin waɗannan siffofi su ne masu gaskiya game da imaninsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar Manzonsa (ﷺ) da ya ja kunnen waɗannan Larabawa na ƙauye ya nuna musu cewa, ta yaya har za su riƙa cewa su ne za su sanar da Allah addininsu, alhalin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya buƙatar haka daga gare su, domin masanin duk abin da yake cikin sammai da abin da yake ƙasa ne, ya san halin da kowa yake ciki ba sai sun faɗa masa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa su waɗannan ƙauyawa, saboda rashin fahimtar addini ne ya sa har suna goranta masa cewa sun musulunta ba tare da ya sha wahalar yaƙar su ba. To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya mayar musu da martani cewa, kada su yi masa gorin musuluntarsu, domin su ne za su ci moriyar Musuluncin, kuma gaskiyar lamari ma ita ce, Allah ne zai goranta musu yayin da ya ba su damar su musulunta, idan har da gaske suke da’awar cewa sun karɓi Musulunci.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu faffaɗan iliminsa, da cewa shi ne yake sane da ɗaukacin abin da yake ɓoye a sammai da abin da yake ɓoye a ƙasa, babu abin da zai ɓuya gare shi, kuma Allah yana ganin abin da suke aikatawa, zai kuma yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin girman darajar Alƙur'ani.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da Alƙur'ani ya kuma siffanta shi da cewa mai girma ne, domin ya ƙunshi ma'anoni masu faɗi, sannan yana tattare da yawan albarka, ga shi kuma ya ƙunshi ɗimbin ilimummuka masu zurfi.

3. Daga cikin manyan dalilan da mushirkai suka fake da su wajen kafirce wa Manzon Allah (ﷺ) shi ne, kasancewarsa mutum irinsu, tare da cewa akwai hikimomi masu girma a cikin aiko da Manzo daga jinsin mutane, domin haka ne zai ba su damar sauraron sa da koyi da shi da kusantar sa, saɓanin mala'ika da suke sa ran a aiko musu.

4. Mamakin da kafirai suka nuna game da aiko da mutum daga cikinsu yana nuna ɗayan abubuwa biyu ne:
Na ɗaya, ko dai mamakin nasu da gaske ne. Wannan kuma zai nuna tsananin jahilcinsu da wautarsu da raunin hankalinsu, kamar mahaukaci ne da zai riƙa nuna mamakinsa game da maganar wani mai hankali, ko kuma raggo da zai riƙa mamakin jarumtar sadauki a fagen yaƙi.
Na biyu, ko kuma mamakinsu ya zamanto na ƙarya ne, watau su kansu sun san ba da gaske suke ba, to wannan yana nuna zaluncinsu da mummunar son zuciyarsu.

5. Cikakken ilimin Allah wanda ya kewaye komai yana nuna cikar Kudurarsa wajen raya matattu.

6. Dalilin mushirikai na ƙaryata dawowa bayan mutuwa shi ne, wai suna ganin cewa wanda ya riga ya mutu, gangar jikinsa ta rududduge ta zama ƙasa, iska ta ɗaiɗaita ta wurare daban-daban, ta yaya za a iya tattara ta wuri guda, domin ai ba wanda zai iya sanin wuraren da ta warwatsu. Kuma ma har idan za a iya tattara ta, to ta ƙaƙa ne za a iya dawo mata da kamanninta na farko? To shi ne Allah ya ba su amsa ta hanyar rushe tushen ruɗaminsu, ya tabbatar musu da cewa shi mai cikakken ilimi ne, babu abin da zai ɓuya gare shi, saboda haka tayar da wanda ya mutu, ya dawo masa da ransa da kamanninsa na farko abu ne mai sauƙi a wurinsa.

7. Yawan tubka da warwara alama ce ta maƙaryaci wanda bai ma san me yake faɗa ba, shi ya sa mushirikan Makka suka yi ta yin tubka da warwara wajen siffanta Manzon Allah (ﷺ) da siffofi daban-daban saboda rashin gaskiyarsu.



50-Suratu Kaf

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Ana kiran wannan Sura da '*Suratu Kaf*', kamar yadda ya zo a hadisi. [Dubi, Muslim #457 da 459 da 873 da 891].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Babu saɓani a tsakanin malami cewa wannan Sura *Makkiyya* ce, watau ta sauka gabanin hijirar Manzon Allah (ﷺ) zuwa Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta talatin da huɗu (34) a jerin saukar surorin Alƙur'ani; ta sauka bayan '*Suratul Mursalat*' kafin saukar '*Suratul Balad*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta arba'in da biyar (45) ne, babu wani saɓani a kan haka.

5. Falalarta:
a. An karɓo daga Ummu Hisham 'yar Harisah ɗan Nu'uman (Allah ya kara mata yarda), ta ce: "Tanderunmu da na Manzon Allah (ﷺ) ɗaya ne tsawon shekara biyu, ko ɗaya da rabi. Ban kuma koyi karatun '*Suratu Kaf Wal Kur'anil Majid*' ba sai daga bakin Manzon Allah (ﷺ); yakan karanta ta a kan mimbari kowace Juma'a yayin da yake yi wa mutane huɗuba." [Muslim #873].
b. An karɓo daga Kuɗba ɗan Malik (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Manzon Allah (ﷺ) ya ja mu sallar asuba sai ya karanta '*Suratu Kaf*' a raka'a ta farko." [Muslim #457].
c. An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Annabi (ﷺ) ya kasance yana karanta '*Kaf Wal Kur'anil Majid*' a sallar asuba. Sallarsa daga baya ta kasance marar tsawo." [Muslim #458].

6. Babban Jigonta:
Farkar da rafkanannun zukata game da tashin alƙiyama da hujjoji masu ƙarfi da suke tabbatar da ita da bayanin abubuwan da za su faru a cikinta.

7. Daga Cikin Abubuwa Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin girman Alƙur'ani da darajojinsa.
• Kafiran Makka sun ƙaryata Manzon Allah ne wai don shi mutum ne kamarsu.
• Dalili a kan tabbatar tashin matattu don yi musu hisabi, domin tayar da su ya ma fi sauƙi a kan farar da halittarsu da kuma halittar sammai da ƙasa da abin da yake cikinsu. Kuma fitar tsirrai da 'ya'yan itatuwa bayan saukar ruwan sama shi ma babban dalili ne a kan raya matattu.

• Kwatanta mushirikan Makka da wasu al'ummu sanannu a wurinsu waɗanda su ma suka ƙaryata manzanninsu, Allah kuma ya saukar musu da azaba. Don haka wajibi ne mushirikai su tsoraci faruwar irin haka a kansu.
• Tsoratar da wanda ya bijire wa Allah game da azabar lahira wadda zai fara haɗuwa da ita tun lokacin da zai zo mutuwa da kuma tsoratar da shi ababen tsoro na lahira.
• Yi wa muminai alƙawarin samun ni'ima a ranar alƙiyama.
• Lallashin Annabi (ﷺ) game da ƙaryatawar da mushirikai suke masa da umartar sa da ya mai da hankalinsa a kan bautar Allah tare da bayyana masa cewa Allah ya jinkirta lamarin masu ƙaryata shi ne zuwa ranar alƙiyama saboda wata hikima tasa, domin da ya ga dama da sai ya azabtar da su tun a nan duniya. Don haka ya sani cewa Allah bai ɗora masa nauyin ya tilasta su har sai sun yi imani ba, abin da kawai aka umarce shi ya yi shi ne wa'azi.
• Yabon waɗanda suka yi imani da tashi bayan mutuwa da cewa su ne kaɗai suke wa'azantuwa da Alƙur'ani.
• Bayanin kewayewar ilimin Allah game da duk wasu ɓoyayyun al'amura da abubuwan da zukata suke ɓoyewa.

Suratu Kaf (1-5)

قٓۚ وَٱلۡقُرۡءَانِ ٱلۡمَجِيدِ ١ بَلۡ عَجِبُوٓاْ أَن جَآءَهُم مُّنذِرٞ مِّنۡهُمۡ فَقَالَ ٱلۡكَٰفِرُونَ هَٰذَا شَيۡءٌ عَجِيبٌ ٢ أَءِذَا مِتۡنَا وَكُنَّا تُرَابٗاۖ ذَٰلِكَ رَجۡعُۢ بَعِيدٞ ٣
قَدۡ عَلِمۡنَا مَا تَنقُصُ ٱلۡأَرۡضُ مِنۡهُمۡۖ وَعِندَنَا كِتَٰبٌ حَفِيظُۢ ٤ بَلۡ كَذَّبُواْ بِٱلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمۡ فَهُمۡ فِيٓ أَمۡرٖ مَّرِيجٍ ٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Kaf. Na rantse da Alƙur'ani mai girma.

2. A'a, sun dai yi mamakin cewa, wani mai gargaɗi daga cikinsu ya zo musu, sai kafirai suka ce: "Wannan abu ne mai ban mamaki!

3. "Yanzu idan muka mutu muka zama ƙasa, (a ce za a komo da mu)? Wannan komowa ce mai nisa!"

4. Haƙiƙa Mun san abin da ƙasa take cinyewa daga gare su; a wurinmu kuma akwai wani littafi mai kiyayewa.

5. A'a, sun dai ƙaryata gaskiya ne lokacin da ta zo musu, don haka suna cikin al'amari rikitacce.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da harafin '*Kaf*' kamar yadda ya buɗe wasu surori da haruffa irin waɗannan. [Dubi tafsirinmu na farkon *Suratul Baƙara* don ƙarin bayani].
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da Alƙur'ani mai girma saboda ɗimbin ma'anonin da ya ƙunsa da yawan alheri da albarka da ke tattare da shi, domin ya tabbatar da cewa, lalle za a tashi halittu bayan sun mutu a ranar alƙiyama don yi musu hisabi da sakamako wanda kafirai suke ƙaryata faruwarsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin da ya sanya mushirikai suke ƙaryata Manzonsa (ﷺ) da cewa, ba wani abu ya haifar musu da haka ba sai don kawai suna mamakin wai ta yaya wani manzo irin jinsinsu na mutane zai zo yana yi musu wa'azi, watau me ya hana a aiko musu da mala'ika? Suna ganin lalle wannan abu ya cika abin mamaki ainun.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilinsu na ƙaryata tashi bayan mutuwa, watau suna mamakin wai yanzu idan sun mutu sun zama ƙasa, a ce za a sake dawo musu da ransu? Suna ganin lalle wannan abu ya yi nisa ƙwarai da tunaninsu, don haka ba za su yi imani da shi ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani da cewa, lalle shi ya san abin da ƙasa take cinyewa daga jikinsu bayan sun mutu an binne su a ƙaburburansu, kuma ba wani abin da bai sani ba game da su, domin a wajensa akwai littafin Lauhul Mahfuz wanda yake kiyaye duk wani abu da ya ƙaddara musu a rayuwarsu da bayan mutuwarsu. Watau wanda yake da wannan cikakken ilimi mai kewaye da sanin komai ta yaya za a yi mamakin cewa zai iya tayar da matacce bayan ya rududduge ya zama ƙasa?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, su waɗannan mushirikan sun ƙaryata Alƙur'ani mai girma wanda Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da shi, don haka suka faɗa cikin wani al'amari mai rikitarwa, domin sun kasa tsayar da magana ɗaya game da Manzon Allah (ﷺ), wani lokaci su ce matsafi ne, wani lokaci kuma su ce boka ne, wani lokaci kuma su ce mawaƙi, da maganganu marasa kan gado irin waɗannan.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk manya-manyan halittun Allah masu ƙarfi da ƙayatarwa, dalilai ne masu tabbatar da girman ikonsa da cikar Kudurarsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe ƙofofin nazari da duba na nutsuwa cikin dukkan halittunsa, domin kowa ya iya kaiwa ga fahimtar cikar Kudurarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai. Wannan bai taƙaita ga wani rukuni na musamman na mutane ba; ya ƙunshi kowa da kowa, gwargwadon basira da fahimta da ilimin da ya hore wa kowa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi haka ne domin ya tsayar da hujjarsa a kan kowa.

3. Girman halittun Allah da ƙarfinsu suna nuna kamalar Kudurar Allah; kyansu da nagartar da ke tattare da su tana nuna cewa shi ne ya fi kowa gwaninta da hikima, kuma masanin komai; abubuwan da ke cikin halittunsa kuwa masu amfani da maslaha ga bayinsa suna nuna cikar rahamarsa gare su; abubuwan da manya-manyan halittunsa suka ƙunsa na ban mamaki da al'ajabi suna tabbatar da cewa, shi ne abin bauta Ɗaya tilo wanda ba shi da mata balle ɗa, wanda babu wani mai kama da shi a siffa ko a suna ko aiki.

Suratu Kaf (6-11)
أَفَلَمۡ يَنظُرُوٓاْ إِلَى ٱلسَّمَآءِ فَوۡقَهُمۡ كَيۡفَ بَنَيۡنَٰهَا وَزَيَّنَّٰهَا وَمَا لَهَا مِن فُرُوجٖ ۝٦ وَٱلۡأَرۡضَ مَدَدۡنَٰهَا وَأَلۡقَيۡنَا فِيهَا رَوَٰسِيَ وَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوۡجِۭ بَهِيجٖ ۝٧ تَبۡصِرَةٗ وَذِكۡرَىٰ لِكُلِّ عَبۡدٖ مُّنِيبٖ ۝٨ وَنَزَّلۡنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ مُّبَٰرَكٗا فَأَنۢبَتۡنَا بِهِۦ جَنَّٰتٖ وَحَبَّ ٱلۡحَصِيدِ ۝٩ وَٱلنَّخۡلَ بَاسِقَٰتٖ لَّهَا طَلۡعٞ نَّضِيدٞ ۝١٠ رِّزۡقٗا لِّلۡعِبَادِۖ وَأَحۡيَيۡنَا بِهِۦ بَلۡدَةٗ مَّيۡتٗاۚ كَذَٰلِكَ ٱلۡخُرُوجُ ۝١١

6. Yanzu ba sa duban sama da take sama da su (su ga) yadda Muka gina ta, Muka kuma ƙawata ta, ba ta kuma da wasu tsage-tsage?

7. Kasa kuma Muka shimfiɗa ta, Muka kuma sanya turaku a cikinta, Muka kuma tsirar da kowane irin nau'in (tsiro) mai ƙayatarwa a cikinta.

8. Don jan hankali da wa'azantarwa ga duk wani bawa mai mayar da al'amarinsa ga Allah.

9. Muka kuma saukar da ruwa mai albarka daga sama sai Muka tsiro da lambuna da shi da kuma ƙwayoyin da ake girba.

10. Da kuma itatuwan dabinai dogwaye da suke da 'ya'ya dodo-dodo.

11. Don arzuta bayi, Muka kuma raya busasshen gari da shi. Kamar haka ne fitowa (daga ƙabari) take.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin mushirikai masu ƙaryata tashi bayan mutuwa da cewa, me ya hana su dubi wasu ƙwararan hujjoji a sama da ƙasa waɗanda suke tabbatar da cikar Kudurar Allah a kan raya matattu? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci guda biyar daga cikin waɗannan hujjojin:
Na ɗaya, su ɗaga kai su dubi yadda ya gina sama ya kuma ƙawata ta da taurari masu haske, sannan ya haɗe ta tamau ba tare da wata tsaga da mutum zai iya gani a tare da ita ba. Duk wanda zai yi irin wannan babban aiki to lalle zai iya tayar da matattu.
Na biyu, su kuma dubi ƙasa su ga yadda ya shimfiɗa ta har ta dace da rayuwar mutane da dabbobi a kanta cikin walwala da natsuwa.
Na uku, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kakkafa manyan duwatsu a cikin ƙasa don su hana ta yin tangal-tangal da abin da yake bayanta.
Na huɗu, sannan su dubi yadda Allah ya fitar da tsirrai da bishiyoyi masu kyan gani daga cikin ƙasa, domin ‘yan’adam da dabbobinsu su sami abinci.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi waɗannan halittu duka domin su zamanto wa’azi da tunatarwa ga duk wani bawa mai komawa zuwa ga Allah da yi masa bauta da ɗa’a.
Na biyar, Ubangiji ya saukar da ruwa daga sama mai cike da amfani da alheri, wanda da shi ya fitar da lambuna masu ban sha’awa da kuma ƙwayoyi da ake girbe su kamar alkama da masara da makamantansu. Har ila yau da wannan ruwan sama ne ya fitar da dogayen bishiyoyin dabino masu ‘ya’ya dodo-dodo wasu kan wasu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya yi duk waɗannan abubuwa ne don su zama arziki ga bayinsa, su ci su kuma ciyar da dabbobinsu. Kuma da wannan ruwan yake raya ƙasa wadda fari ya kashe ta, sai ta sake komawa koriya shar cike da kayan amfanin gona da tsirrai iri-iri. To kamar haka ne Allah yake raya matattu su fito daga ƙaburburansu kamar yadda ya fara halittar su da farko.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karyata manzannin Allah al’ada ce ta al’ummun da suka gabata, uƙubar Allah ga masu ƙaryata su kuma sunnarsa ce tabbatacciya.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa mushirikan Makka cewa ba su ne farau ba wajen ƙaryata manzannin Allah; al’ummu da yawa sun riga su aikata irin wannan mummunan laifin, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu wasu daga cikin waɗannan al’ummun waɗanda suka fi shahara a duniya da kuma a wurinsu su Larabawa.

3. ‘Yan’uwantakar Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa ba 'yan'uwataka ce ta jini ba, 'yan'uwantaka ce ta zama wuri ɗaya, domin shi ba ɗan ƙabilarsu ba ne. Su mutanen Sadum da Ammura da ƙauyukansu ne. Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuwa ya zauna ne a Sadum ba ɗan gari ne ba, domin su Kana'aniyawa ne, shi kuma Ba'ibraniye ne.

Suratu Kaf (12-15)
كَذَّبَتۡ قَبۡلَهُمۡ قَوۡمُ نُوحٖ وَأَصۡحَٰبُ ٱلرَّسِّ وَثَمُودُ ١٢ وَعَادٞ وَفِرۡعَوۡنُ وَإِخۡوَٰنُ لُوطٖ ١٣ وَأَصۡحَٰبُ ٱلۡأَيۡكَةِ وَقَوۡمُ تُبَّعٖۚ كُلّٞ كَذَّبَ ٱلرُّسُلَ فَحَقَّ وَعِيدِ ١٤ أَفَعَيِينَا بِٱلۡخَلۡقِ ٱلۡأَوَّلِۚ بَلۡ هُمۡ فِي لَبۡسٖ مِّنۡ خَلۡقٖ جَدِيدِ ١٥

12. Mutanen Nuhu da ma’abota rijiyar *Rassu* da Samudawa (duka) sun ƙaryata (annabawa) a gabaninsu (watau mutanen Makka).

13. Da kuma Adawa da Fir’auna da ‘yan’uwan Luɗu (su ma sun ƙaryata).

14. Da kuma ma’abota surƙuƙi da mutanen Tubba’u. Kowannensu ya ƙaryata manzanni, sai azabata ta tabbata (a kansu).

15. Shin Mun gaza ne da halittar farko? A’a, su dai suna cikin shakka ne game da sake halitta.

A waɗannan ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, a baya can kafin mushirikan Larabawa an samu al’ummu da dama waɗanda suka ƙaryata annabawan da ya aika musu, kamar yadda mushirikan suka ƙaryata shi, don haka ya hallaka su. Wannan jan kunne ne ga mushirkan Larabawa da su guji faɗawa cikin irin abin da waɗancan al’ummu suka faɗa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci cewa mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ƙaryata shi. Hakanan ma’abota rijiyar ‘*Rassu*’ su ma sun ƙaryata annabinsu. Samudawa mutanen Annabi Salihu su ma sun ƙaryata shi. Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ƙaryata shi. Fir’auna da mutanensa waɗanda su kuma suka ƙaryata annabawan Allah watau Musa da Haruna, kamar yadda mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka ƙaryata shi.
Ban da waɗannan kuma akwai ma’abota surƙuƙi, watau mutanen Annabi Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) su ma sun ƙaryata Manzon Allah Shu’aibu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sannan da mutanen Tubba’u Sarkin Yaman, su ma sun ƙaryata annabin da Allah ya aika musu. Daga nan dukkansu uƙubar da Allah ya yi musu alƙawarin za ta same su idan sun ƙi yin imani ta tabbata a kansu, Allah ya hallaka su bai bar ko mutum ɗaya ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kafa musu hujja a kan abin da suke ƙaryatawa na tashi bayan mutuwa da cewa, shi ne fa wanda ya halicce su da farko ba tare da ya gaza ba, to ta yaya kuma za a ce ba zai iya sake dawo da halittarsu ba a karo na biyu? Su sun san haka kamar yadda suka san cewa yin halittar farko ta fi sake maimaita ta zama abin mamaki, sai dai kawai su mutane ne da shakku ya riga ya mamaye musu zukata ya hana su karɓar gaskiya da aiki da hankali.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ilimin Allah ya kewaye komai. Allah yana sane da duk wani abu da bawansa yake saƙawa a ransa mai kyau ne ko mummuna.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadar wa kowane mutum mala’iku biyu tare da shi, a damansa da hagunsa, domin rubuta ayyukansa na alheri da na sharri.

3. Ya wajaba koyaushe mutum ya riƙa tunawa da zaman waɗannan mala’iku biyu a tare da shi, ya girmama su ya ji kunyarsu, don haka ya guji aikata wasu munanan ayyuka ko furta miyagun kalamai, koyaushe ya faɗi alheri ya aikata alheri.

4. Tabbatar da magagin mutuwa lokacin fitar rai.

5. Haɗarin gafala game da ranar lahira da rashin sanin sakamakonta da azaba da ni'ima da ke cikinta.

Suratu Kaf (16-22)

وَلَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ وَنَعۡلَمُ مَا تُوَسۡوِسُ بِهِۦ نَفۡسُهُۥۖ وَنَحۡنُ أَقۡرَبُ إِلَيۡهِ مِنۡ حَبۡلِ ٱلۡوَرِيدِ ١٦ إِذۡ يَتَلَقَّى ٱلۡمُتَلَقِّيَانِ عَنِ ٱلۡيَمِينِ وَعَنِ ٱلشِّمَالِ
قَعِيدٞ ١٧ مَّا يَلۡفِظُ مِن قَوۡلٍ إِلَّا لَدَيۡهِ رَقِيبٌ عَتِيدٞ ١٨ وَجَآءَتۡ سَكۡرَةُ ٱلۡمَوۡتِ بِٱلۡحَقِّۖ ذَٰلِكَ مَا كُنتَ مِنۡهُ تَحِيدُ ١٩ وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِۚ ذَٰلِكَ يَوۡمُ
ٱلۡوَعِيدِ ٢٠ وَجَآءَتۡ كُلُّ نَفۡسٖ مَّعَهَا سَآئِقٞ وَشَهِيدٞ ٢١ لَّقَدۡ كُنتَ فِي غَفۡلَةٖ مِّنۡ هَٰذَا فَكَشَفۡنَا عَنكَ غِطَآءَكَ فَبَصَرُكَ ٱلۡيَوۡمَ حَدِيدٞ ٢٢

16. Haƙiƙa kuma Mun halicci mutum, kuma Mun san abin da ransa yake saƙa masa; kuma Mu Muka fi kusa da shi fiye da jijiyar wuyansa.

17. Yayin da (mala’iku biyu) masu haɗuwa suka haɗu ta dama da ta hagu suna zaune.

18. Ba wata magana da zai furta face a tare da shi akwai (mala'ika) mai kula kuma halartacce.

19. Kuma magagin mutuwa ya zo da gaskiya; wannan ne abin da ka kasance kana kakkauce wa.

20. Aka kuma yi busa a ƙaho. Wannan ita ce ranar narko.

21. Kuma kowane rai ya zo a tare da shi akwai mai kora da mai shaida.

22. Haƙiƙa ka kasance a cikin gafala game da wannan, sai Muka yaye maka yanarka, to ganinka a yau tangaran yake.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikakken iliminsa game da ɗan’adam, domin shi ne Mahaliccinsa wanda ya halicci jinsinsa namiji da mace, don haka ya san ƙomai nasa; ya san duk abubuwan da yake ƙullawa a ransa, domin shi Allah ya fi kusa da ɗan’adam fiye da jijiyar wuyansa wadda take haɗe da zuciyarsa, yayin da mala’iku biyu suke karɓar ayyukan da yake aikatawa suna rubutawa; ɗayansu a dama yana rubuta kyawawan ayyukansa; ɗayansu kuma a hagu yana rubuta munanan ayyukansa; ƙowannensu yana tsaye a kan aikinsa ba ya sakaci ko kaɗan; domin babu wata magana da mutum zai furta face a tare da shi akwai mala’ika yana kula da abin da yake faɗa yana kuma rubutawa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana lokacin da wa’adin ɗan’adam zai cika, mutuwa ta zo masa da tsananin magaginta da gaskiyar da babu mai iya guje mata, a nan ne za a tabbatar masa cewa wannan shi ne abin da ya kasance tsawon rayuwarsa yana kakkauce masa. To daga nan fa ƙaramar alƙiyamar mutum ta tsaya.
Sai kuma lokacin da wa’adin tashin alƙiyama zai zo, to a lokacin Mala’ika Israfilu ne zai yi busa a ƙaho busa ta biyu, to wannan ita ce ranar alƙiyama, ranar narko ga kafirai da masu saɓon Allah.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a wannan ranar ƙowane mahaluƙi zai zo tare da mala’ika yana kore da shi da kuma wani mala’ika mai bayar da shaida a kan dukkan ayyukansa masu kyau da munana.
To a nan ne za a gaya wa duk wanda yake ƙaryata tashin alƙiyama cewa, tun a duniya yana cikin gafala game da wannan ranar, son zuciya da sha’awa da ruɗun Shaiɗan sun rufe masa ido, to yau ga shi an yaye masa dukkan gafalarsa, idonsa ya buɗe yana gani tangararan; yana ganin azabar Allah a fili, baƙin ciki ya rufe masa zuciya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani kafiri ko mai laifi shaiɗaninsa zai bijire masa a ranar alƙiyama ya nesanta kansa da shi, ya kuma nuna ba shi da wata alaƙa da kafircinsa da miyagun ayyukansa, duk wani laifi da aka same shi da shi, ya yi shi ne da zaɓin kansa da ganin damarsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yanke wa kowa hanzari tun da ya aiko da manzanninsa don su isar da gargaɗinsa, don haka babu mai bakin jayayya a gaban Allah ranar alƙiyama, domin ko me zai faɗa ba zai amfane shi ba.

3. Cikar adalcin Allah ga bayinsa, zai yi wa kowa sakamako gwargwadon aikinsa ba tare da ya zalunci wani ba.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai cika wa wutar Jahannama alƙawarin da ya yi mata na cika ta maƙil da kafirai da masu laifuka, kuma duk yawansu kowa sai ya samu wuri a cikinta.

Suratu Kaf (23-30)

وَقَالَ قَرِينُهُۥ هَٰذَا مَا لَدَىَّ عَتِيدٌ ﴿٢٣﴾ أَلۡقِيَا فِي جَهَنَّمَ كُلَّ كَفَّارٍ عَنِيدٍ ﴿٢٤﴾ مَّنَّاعٖ لِّلۡخَيۡرِ مُعۡتَدٖ مُّرِيبٍ ﴿٢٥﴾ ٱلَّذِي جَعَلَ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَأَلۡقِيَاهُ فِي ٱلۡعَذَابِ ٱلشَّدِيدِ ﴿٢٦﴾ ۞قَالَ قَرِينُهُۥ رَبَّنَا مَآ أَطۡغَيۡتُهُۥ وَلَٰكِن كَانَ فِي ضَلَٰلِۭ بَعِيدٖ ﴿٢٧﴾ قَالَ لَا تَخۡتَصِمُواْ لَدَيَّ وَقَدۡ قَدَّمۡتُ إِلَيۡكُم بِٱلۡوَعِيدِ ﴿٢٨﴾ مَا يُبَدَّلُ ٱلۡقَوۡلُ لَدَيَّ وَمَآ أَنَا۠ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ﴿٢٩﴾ يَوۡمَ نَقُولُ لِجَهَنَّمَ هَلِ ٱمۡتَلَأۡتِ وَتَقُولُ هَلۡ مِن مَّزِيدٖ ﴿٣٠﴾

23. Mala’ikan da yake tare da shi kuma ya ce: “Wannan shi ne abin da yake hallare a tare da ni.”

24. (Aka ce da mala’ikun): “Ku jefa duk wani kafiri mai taurin kai cikin Jahannama.

25. “Mai yawan hana alheri, mai ta’addanci, mai shakka.

26. “Wanda ya sanya wani abin bauta daban tare da Allah, saboda haka ku jefa shi cikin azaba mai tsanani.”

27. Shaiɗaninsa ya ce: “Ya Ubangijina, ni ban ɓatar da shi ba, sai dai kawai ya kasance cikin ɓata mai nisa.”

28. (Allah) ya ce: “Kada ku yi husuma a gabana, haƙiƙa tuni Na gabatar muku da gargaɗin azaba.

29. “Ba a sauya magana a gabana, kuma Ni ba mai zaluntar bayi ba ne.”

30. A ranar da za Mu ce da Jahannama: “Shin kin cika?” (Ita) kuma ta ce: “Shin akwai wani ƙari?”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a ranar alƙiyama mala’ika da ke tare da kafiri wanda aka wakilta shi ya kula da ayyukan wannan kafirin ya rubuta komai nasa, zai zo da duk abin da ya tattara na ayyukansa ya shaida wa Ubangiji cewa, ga abin da yake tare da shi a rubuce na dukkan ayyukansu.
A nan ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai umarci mala’ikun nan guda biyu, watau wanda ya kora kafiri da wanda ya bayar da shaida a kansa da cewa, su jefa duk wani kafiri mai taurin kai cikin wutar Jahannama, saboda kafircinsa da yawan saɓon Allah da yake yi, ga shi kuma mai hana duk wani alheri da ƙetare iyakokin Mahaliccinsa da rungumar wani abin bauta yana bauta masa tare da Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a nan ne shi kafirin zai nemi ya kawo wani hanzari na kauce

wa hanyar Allah da cewa, shaiɗaninsa ne ya hallaka shi ya ɓatar da shi. Sai shi kuma shaiɗanin nasa ya musunta hakan, ya tabbatar wa da Ubangiji cewa, ba shi ne ya ɓatar da shi ba; da ma can ya kasance cikin ɓata mai nisa, watau yayin da ya haɗu da shaiɗaninsa za-mu ce ta tadda mu-je-mu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, bayan husuma ta kaure tsakanin kafiri da shaiɗaninsa, sai ya daka musu tsawa cewa, su daina wata husuma da jayayya a gabansa, wadda ba ta da wani amfani, domin kuwa tun a duniya ya aika musu da manzanninsa da narkon azaba ga duk wanda ya kafirce masa ya bijire wa umarninsa. Ya kuma tabbatar musu da cewa, shi ba a sauya magana a wurinsa, kuma ba ya saɓa alƙawarinsa, ba kuma ya zaluntar bayinsa ko ya tauye musu kyawawan ayyukansu ko ya ƙara musu laifukan da ba nasu ba; yana dai yi wa kowa sakayya ne da irin aikinsa mai kyau da mummuna.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da bayinsa azabar wutar Jahannama wadda za a yi ta jibga kafirai da masu saɓon Allah cikinta dodo-dodo har a tambaye ta cewa ko ta cika? Ita kuma sai ta nuna cewa akwai sauran wuri a cikinta, idan akwai ƙari to a ƙaro mata.

An karɓo daga Anas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Jahannama ba za ta gushe ba ana ta jefa ‘yan wuta a cikinta ita kuma tana cewa, shin akwai ƙari ne? Har sai Ubangiji Mai buwaya ya sanya duddugensa a cikinta sai sashenta ya tattaru ya haɗe da sashi tana cewa: “Ya isa haka, ya isa haka, na rantse da Buwayarka da girmanka. Ita kuma Aljanna ba za ta gushe da rarar wuri a cikinta ba, har sai Allah ya ƙagi wasu halittu daban waɗanda zai shigar da su rarar Aljanna.” [Muslim #2848].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai kusanto da Aljanna ga bayinsa masu taƙawa a ranar alƙiyama tun gabanin su shige ta, don gaggauto musu da ni’imominta da faranta musu rai da kuma sauƙaƙa musu isa gare ta.

2. Tsoron Allah a ɓoye shi ne ƙololuwar tsoronsa wanda riya ba ta shiga cikinsa ba, saɓanin nuna tsoron sa a bainar jama’a wanda riya takan iya shiga cikinsa.

3. Tun gabanin muminai su shiga gidajensu na Aljanna za a ba su tabbacin cewa, Aljanna gida ne na aminci da kuɓuta daga duk wani abin ƙi sannan da samun rayuwa cikin ni’ima mai ɗorewa har abada.

4. Duk abin da ‘yan Aljanna za su yi sha’awa a cikinta za su same shi ba tare da ɓata lokaci ba.

Suratu Kaf (31-35)
وَأُزۡلِفَتِ ٱلۡجَنَّةُ لِلۡمُتَّقِينَ غَيۡرَ بَعِيدٖ ٣١ هَٰذَا مَا تُوعَدُونَ لِكُلِّ أَوَّابٍ حَفِيظٖ ٣٢ مَّنۡ خَشِيَ ٱلرَّحۡمَٰنَ بِٱلۡغَيۡبِ وَجَآءَ بِقَلۡبٖ مُّنِيبٍ ٣٣ ٱدۡخُلُوهَا بِسَلَٰمٖۖ ذَٰلِكَ يَوۡمُ ٱلۡخُلُودِ ٣٤ لَهُم مَّا يَشَآءُونَ فِيهَا وَلَدَيۡنَا مَزِيدٞ ٣٥

31. Aka kuma kusantar da Aljanna ga masu tsoron Allah, ba tare da nisa ba.

32. (Sai a ce da su): “Wannan ne abin da ake yi muku alƙawarinsa, (ga shi nan a tanade) ga duk wani mai yawan komawa ga Allah, mai kiyaye (dokokinsa).

33. “Wanda ya ji tsoron Allah a ɓoye, ya zo kuma da zuciya mai komawa ga Allah.”

34. (Za a ce da su): Ku shige ta da aminci; wannan ita ce ranar dawwama.

35. Suna da duk abin da suka dama a cikinta, kuma wurinmu akwai wani ƙari.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa bayinsa albishir ne da sakamakon gidan Aljanna ranar alƙiyama yayin da za a kusanto ta gare su saboda taƙawarsu da kiyayewarsu ga dokokin Allah, inda za su ga ɗimbin ni'imomin da ke cikinta waɗanda idanuwansu ba su taɓa gani ba, kunnuwansu ba su taɓa jin labarinsu ba, kuma ba su taɓa tunanin irinsu ba. A nan ne za a tarye su ana yi musu maraba da zuwa, ana kuma sanar da su cewa wannan tagomashi da suke gani shi ne gidan Aljanna da aka yi alƙawarinsa ga duk wani bawa mai yawan komawa ga Allah mai biyayya da tuba gare shi, mai kiyaye dokokinsa. Wanda ya ji tsoron Allah a ɓoye inda babu mai ganin sa sai Allah, ya kuma sadu da Allah yana mai lafiyayyar zuciya, mai komawa gare shi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, za a ce wa 'yan Aljanna su shige ta cikin aminci ba tare da sun haɗu da wani abu mai sosa zuciya ba, a kuma tabbatar musu da cewa wannan rana ita ce ranar dawwama, babu mutuwa a cikinta har abada.
Sannan a nuna musu cewa, duk ni'imomin gidan Aljanna nasu ne su yi yadda suke so kuma duk abin da ransu yake so na ni'ima za a ba su har ma da ƙarin wasu ni'imomin waɗanda ba su san da su ba; daga cikinsu akwai ganin Fuskar Ubangijinsu da samun yardarsa ta har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mai hankali da karatun ta-nutsu shi ne yake ɗaukar wa'azi daga abubuwan da suka faru ga al'ummun da suka gabata.

2. Duk mai son ya amfana da Alƙur'ani to sai ya haɗa hankalinsa wuri guda lokacin da ake karanta masa shi ko yake karantawa, ya kuma nutsu wajen sauraron sa, ya halarto da zuciyarsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu cikin kwana shida, tare da cewa zai iya abin da ya fi haka cikin ƙiftawar ido, don ya koya wa bayinsa yin abubuwa cikin nutsuwa ba da garaje ba.

4. Rushe aƙidar Yahudawa masu cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi halitta cikin kwana shida ya huta a kwana na bakwai, watau Asabar. Gajiya da buƙatar hutu siffa ce ta naƙasa da kasawa, don haka ba a siffanta Allah Mahalicci da ita domin siffofinsa duk na kamala ne.

5. Nuni zuwa ga Kudurar Allah game da raya matattu, domin wanda zai iya yin manya-manyan halittu kamar sammai da ƙasa, lalle abu ne mai sauƙi a wurinsa ya sake dawo da mutum bayan mutuwarsa.

6. Ibada da yawan ambaton Allah suna taimaka wa bawa wajen fuskantar duk wani ƙalubale na rayuwa da samun galaba a kan abokan gaba da ikon jure wa tsangwamarsu da cutarwarsu.

Suratu Kaf (36-40)
وَكَمْ أَهْلَكْنَا قَبْلَهُم مِّن قَرْنٍ هُمْ أَشَدُّ مِنْهُم بَطْشًا فَنَقَّبُواْ فِي ٱلْبِلَٰدِ هَلْ مِن مَّحِيصٍ ۝٣٦ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَذِكْرَىٰ لِمَن كَانَ لَهُۥ قَلْبٌ أَوْ أَلْقَى ٱلسَّمْعَ وَهُوَ شَهِيدٌ ۝٣٧ وَلَقَدْ خَلَقْنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا فِي سِتَّةِ أَيَّامٍ وَمَا مَسَّنَا مِن لُّغُوبٍ ۝٣٨ فَٱصْبِرْ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ قَبْلَ طُلُوعِ ٱلشَّمْسِ وَقَبْلَ ٱلْغُرُوبِ ۝٣٩ وَمِنَ ٱلَّيْلِ فَسَبِّحْهُ وَأَدْبَٰرَ ٱلسُّجُودِ ۝٤٠

36. Al'ummu nawa Muka hallaka a gabaninsu waɗanda suka fi su tsananin ƙarfi, sai suka riƙa bincike cikin garuruwa ko akwai wata matsera.

37. Lalle game da wannan tabbas akwai wa'azi ga wanda ya kasance yana da hankali ko kuma ya karkaɗe kunne (don sauraron wa'azi), alhali zuciyarsa tana tare da shi.

38. Haƙiƙa kuma Mun halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu cikin kwana shida, kuma wata gajiya ba ta shafe mu ba.

39. To ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, ka kuma yi tasbihi da yabon Ubangijinka kafin fudowar rana da kuma kafin faɗuwarta.

40. Da daddare kuma sai ka tsarkake shi, da kuma bayan salloli.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da mushirikai azabarsa, ya tabbatar musu cewa, ya hallaka al'ummu da dama waɗanda sun fi su tsananin ƙarfi nesa ba kusa ba, amma yayin da azabar Allah ta zo musu sun yi ta ƙoƙarin neman garuruwan da za su gudu su tsere mata amma hakan bai samu ba har sai da azabar Allah ta cim musu ta kuma hallaka su gaba ɗaya, don haka su ma ba za su iya tsere wa azabarsa ba yayin da ta zo musu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalinsu da cewa, lalle idan sun yi la'akari da abin da ya faru ga kafiran da suka gabace su za su ga akwai wa'azi da izina mai tarin yawa, sai dai ba kowa ne zai gane haka ba sai wanda yake yana da hankali ko kuma ya karkaɗe kunnensa ya yi sauraro na nutsuwa yayin da zuciyarsa tana tare da shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu girman Kudurarsa da cikar ikonsa, domin shi ne wanda ya halicci sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu a cikin kwana shida, watau ya fara ranar Lahadi ya gama ranar Juma'a, duk kuwa da cewa yana iya halittar su a cikin ƙasa da ƙiftawar ido da ya so yin hakan. Kuma ya yi duk wannan aikin ne ba tare da wata gajiya ta same shi ba, kamar yadda Yahudawa suke riyawa don ƙarya da kafirci.
Sai kuma ya lallashi Manzonsa (ﷺ) wanda yake ta damuwa game da munanan maganganu da mushirikai suke faɗa masa da bijirewar da suke yi masa. Ya umarce shi da ya yi haƙuri, ya mayar da hankalinsa wajen bautar Allah ya riƙa yi masa tasbihi tare da gode masa a sallarsa ta asuba kafin hudowar rana da kuma sallarsa ta la'asar kafin faɗuwar rana. Hakanan ya tsarkake shi da tasbihi a sallarsa ta dare, watau magariba da isha'i, ya kuma yi ta yi masa tasbihi bayan salloli.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda ya yi tasbihi talatin da uku bayan kowace salla, ya yi kabbara talatin da uku, ya kuma yi hamdala talatin da uku dukansu gaba ɗaya tis'in da tara ke nan, sannan cikon na ɗari ya ce: '*La Ilaha Illallahu Wahdahu La Sharika Lahu Lahul Mulku Wa lahul Hamdu Wa Huwa Ala Kulli Shai'in Kadir*', to za a gafarta masa laifukansa ko da sun kai misalin kumfar kogi." [Muslim #597].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da tashi bayan mutuwa, kuma yin haka abu ne mai sauƙi a wurin Allah.

2. Mai wa'azi mai kira ne zuwa ga Allah amma ba mai tilastawa a yi imani ba ne.

3. Wanda yake jin tsoron azabar Allah shi ne kaɗai wa'azi yake yi wa amfani.

4. Mafificin abin da mai wa'azi zai yi wa'azi da shi shi ne Alƙur'ani.

Suratu Kaf (41-45)

وَٱسۡتَمِعۡ يَوۡمَ يُنَادِ ٱلۡمُنَادِ مِن مَّكَانٖ قَرِيبٖ ٤١ يَوۡمَ يَسۡمَعُونَ ٱلصَّيۡحَةَ بِٱلۡحَقِّۚ ذَٰلِكَ يَوۡمُ ٱلۡخُرُوجِ ٤٢ إِنَّا نَحۡنُ نُحۡيِۦ وَنُمِيتُ وَإِلَيۡنَا ٱلۡمَصِيرُ ٤٣ يَوۡمَ تَشَقَّقُ ٱلۡأَرۡضُ عَنۡهُمۡ سِرَاعٗاۚ ذَٰلِكَ حَشۡرٌ عَلَيۡنَا يَسِيرٞ ٤٤ نَّحۡنُ أَعۡلَمُ بِمَا يَقُولُونَۖ وَمَآ أَنتَ عَلَيۡهِم بِجَبَّارٖۖ فَذَكِّرۡ بِٱلۡقُرۡءَانِ مَن يَخَافُ وَعِيدِ ٤٥

41. Ka kuma saurara ranar da mai kira zai yi kira daga wani wuri makusanci.

42. A ranar da (talikai) za su ji tsawa ta gaskiya. Wannan ita ce ranar fitowa (daga ƙabari).

43. Lalle Mu ne Muke rayawa, Muke kuma kashewa, kuma makoma zuwa gare Mu ne.44. A ranar da ƙasa za ta tsattsage musu (su fito) da gaggawa. Wannan tattarawa ce mai sauƙi a gare Mu.

45. Mu ne Muka fi sanin abin da (kafiran Makka) suke faɗa; kuma kai ba mai tilasta musu ba ne; saboda haka sai ka yi wa'azi da Alƙur'ani ga wanda yake tsoron azabata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya saurara ya ji labarin abubuwan ban tsoro da firgici da za su faru ranar da mai kira, watau mala'ikan da aka wakilta domin busa ƙaho, zai yi kira daga wani wuri makusanci, zai kuma yi busa ta biyu wadda duk halittu za su ji tsawarta da gaskiyar da babu kokwanto a cikinta; to wannan ranar ita ce ranar fitowar matattu daga ƙaburburansu domin yi musu hisabi da sakamako.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, shi ne kaɗai mai rayawa mai kashewa, babu mai iya waɗannan ayyuka sai shi, don haka gare shi ne kaɗai makomar bayi take, watau ranar alƙiyama domin hisabi da sakamako.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, a ranar ne ƙasa za ta tsattsage wa ɗaukacin halittun da ke kwance cikinta, sai su fito daga ƙaburburansu cikin gaggawa, Allah ya tattara su gaba ɗayansu wuri guda domin yi musu hisabi. Allah kuma ya tabbatar musu da cewa wannan tattarawar a wurinsa abu ne mai sauƙi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara lallashin Manzonsa game da baƙaƙen maganganu da yake ji daga bakunan mushirikai da cewa, kada wannan ya tayar masa da hankali, Allah yana sane da duk irin maganganun da suke faɗa masa na ɓatanci, don haka ba za su kuɓuce masa ba, shi dai Manzon Allah (ﷺ) kawai ya ci gaba da yi musu wa'azi cikin ruwan sanyi, kuma ba a ɗora masa alhakin ya tilasta musu yin imani ba, shi dai ya ci gaba da yin wa'azi da Alƙur'ani ga duk mai tsoron azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) domin mai jin tsoron Allah ne kawai yake wa'azantuwa da abin da ake karanta masa na Alƙur'ani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya yin rantsuwa da duk abin da ya ga damar yin rantsuwa da shi daga cikin halittunsa, don ya janyo hankali zuwa ga muhimmancinsa ko amfaninsa a rayuwar bayinsa. Amma kuma bayinsa bai halatta su yi rantsuwa da wani abu ba sai shi.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi ta yi wa mushirikai bayanin gaskiyar zuwan alƙiyama amma suka ci gaba da ƙaryatawa duk da ɗimbin dalilai da hujjoji da ya bayyana musu, sai ya zamanto babu abin da ya rage sai ya yi musu rantsuwa a kan haka, domin rantsuwa abu ne mai girman gaske a wurin Balarabe tun a zamanin jahiliyya.

3. Dukkan rantse-rantse da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi a cikin littafinsa, suna ƙunshe da bayanin wasu dalilai masu tabbatar da Kudurarsa da girman ikonsa da manyan ni'imominsa.

4. Sassaɓawar maganganun mushirikai game da Annabi (ﷺ) da Alƙur’ani, dalili ne da ke tabbatar da rashin gaskiyarsu, domin gaskiya ɗaya ce ba ta sassaɓawa.

5. Tabbatar da tashin alƙiyama da azaba ga kafirai a wannan ranar.

51-Suratuz Zariyat

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
An fi sanin ta da '*Suratuz Zariyat* ' domin kalmar *Az-Zariyat* ba ta zo ba sai a cikin wannan Surar kaɗai. A littafin Sahihul Bukhari da wasu littattafan tafsiri an kira ta da suna '*Suratu Waz-Zariyat*'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin dukkan malamai babu saɓani.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta sittin da shida (66) a jerin saukar surorin Alƙur'ani; ta sauka bayan '*Suratul Ahƙaf*' kafin '*Suratul Ghashiya*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta sittin ne (60) a wurin dukkan malaman lissafin ayoyin Alƙur'ani.

5. Babban Jigonta:
Sanar da halittu haƙiƙanin mai arzutawa, watau Allah, domin bayi su koma gare shi su tsantsanta bauta a gare shi shi kaɗai.

6. Daga Cikin Abubuwa Da Ta Kunsa Akwai:
• Tabbatar da aukuwar tashin alƙiyama.
• Rushe maganganun mushirikai game da ƙaryata tashin alƙiyama da manzancin Annabi (ﷺ) da nuna cewa suna magana ne ba bisa wata hujja ba.
• Yi wa kafirai alƙawarin azaba mai tsanani.
• Yi wa muminai albishir da ni'ima madawwamiya, saboda imaninsu da kyautatawarsu.
• Kafa hujjoji masu ƙarfi a kan Kaɗaitakar Allah da yiwuwar tashi bayan mutuwa ta hanyar yin la'akari da wasu daga cikin halittun Allah masu nuna cikar Kudurarsa da ikonsa.
• Gargaɗi da tsoratarwa ga mushirikai masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) ta hanyar sanar da su abin da ya samu al'ummun da suka ƙaryata annabawansu.
• Jan hankalin masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) a kan su dawo su yi imani da shi, su yi watsi da shirka da Allah.
• Nema wa Manzon Allah (ﷺ) hanzari game da bijirewar kafirai waɗanda suka butulce wa ni'imar Allah ta halittawa da arzutawar da ya yi musu.
• Yi musu alƙawarin narko da azaba irin wadda ta auka wa waɗanda suka gabace su.

Suratuz Zariyat (1-14)

وَٱلذَّٰرِيَٰتِ ذَرۡوٗا ۝١ فَٱلۡحَٰمِلَٰتِ وِقۡرٗا ۝٢ فَٱلۡجَٰرِيَٰتِ يُسۡرٗا ۝٣ فَٱلۡمُقَسِّمَٰتِ أَمۡرًا ۝٤ إِنَّمَا تُوعَدُونَ لَصَادِقٞ ۝٥ وَإِنَّ ٱلدِّينَ لَوَٰقِعٞ ۝٦ وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلۡحُبُكِ ۝٧ إِنَّكُمۡ لَفِي قَوۡلٖ مُّخۡتَلِفٖ ۝٨ يُؤۡفَكُ عَنۡهُ مَنۡ أُفِكَ ۝٩ قُتِلَ ٱلۡخَرَّٰصُونَ ۝١٠ ٱلَّذِينَ هُمۡ فِي غَمۡرَةٖ سَاهُونَ ۝١١ يَسۡـَٔلُونَ أَيَّانَ يَوۡمُ ٱلدِّينِ ۝١٢ يَوۡمَ هُمۡ عَلَى ٱلنَّارِ يُفۡتَنُونَ ۝١٣ ذُوقُواْ فِتۡنَتَكُمۡ هَٰذَا ٱلَّذِي كُنتُم بِهِۦ تَسۡتَعۡجِلُونَ ۝١٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da iskoki masu ta da ƙura.

2. Sannan da (giragizai) waɗanda suke ɗauke da nauyin ruwa.

3. Da jiragen ruwa masu gudu a sauƙaƙe.

4. Da kuma mala’iku masu raba abubuwa.

5. Lalle abin da ake yi muku alƙawarinsa tabbas gaskiya ne.

6. Kuma lalle sakamako tabbas mai afkuwa ne.

7. Na rantse da sama ma’abociyar hanyoyi.

8. Lalle ku (mutanen Makka) tabbas kuna cikin magana mai sassaɓawa.

9. Ana karkatar da wanda aka karkatar daga gare shi (Annabi ko Alƙur’ani).

10. An la’anci maƙaryata.

11. Waɗanda suke rafkanannu a cikin jahilci.

12. Suna tambayar yaushe ne ranar sakamako?

13. A ranar da su za a azabtar da su kan wuta.

14. (A ce da su): “Ku ɗanɗani azabarku, wannan shi ne abin da kuka kasance kuna neman gaggautowarsa.”

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da jerin rantse-rantse da wasu daga cikin halittunsa masu muhimmanci da amfani a rayuwar bayinsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rantse da iskoki masu ta da ƙura da giragizai da jiragen ruwa masu gudu a sauƙaƙe a cikin kogi da mala’iku masu rarraba abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su su raba na al’amuran bayinsa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin waɗannan rantse-rantse nasa, wanda shi ne don tabbatar da cewa, lalle abin da yake yi wa mushirikai alƙawarin faruwarsa na hisabi da sakamako gaskiya ne babu kokwanto a kansa. Kuma lalle sakamakon bayi a ranar alƙiyama mai aukuwa ne ba makawa.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake rantsuwa da sama mai kyakkyawar halitta, ma’abociyar hanyoyi, domin ya tabbatar wa mutanen Makka cewa, suna cikin maganganu masu sassaɓawa da suke cike da tubka da warwara game da Annabi (ﷺ) da Alƙur’ani; wani lokaci su ce matsafi ne, Alƙur’ani kuma tsafi ne; wani lokaci kuma sai su ce masa mawaƙi Alƙur’ani kuma waƙa ce; a wani lokaci kuma sai su kira shi da boka ko mai taɓin hankali. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ana karkatar da wanda aka

karkatar daga yin imani da Alƙur'ani da Annabi (ﷺ), domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya san cewa da ma can ba zai yi imani ba, ba kuma zai dace da shiriya ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan sakamakon maƙaryata waɗanda suke ta sharara ƙarya game da Annabi (ﷺ) da Alƙur'ani, da cewa an la'ance su an nesanta su daga samun rahamar Allah, domin kuwa su mutane ne rafkanannu cikin jahilci kuma ba sa tuna lahira, ba su damu da ita ba, har ma suna ganin ƙarya ce ba gaskiya ba, suna tambayar Annabi (ﷺ) da muminai cewa, wai yaushe ne ma ranar sakamako za ta zo? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, a ranar ne za a azabtar da su a cikin wutar Jahannama, ana ce musu su ɗanɗani azabarsu, wannan ita ce ranar da koyaushe ake tsoratar da su ita, kuma suke gaggauto da zuwanta don nuna izgili da shaƙiyanci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Taƙawa, watau bin umarnin Allah da guje wa haninsa sababi ne na samun gidan Aljanna.

2. Kyautata aiki da yin sa don Allah shi ma sababi ne na shiga Aljanna.

3. Yayin da masu kyautata aikinsu suka kasance a duniya suna masu riƙo da umarnin da Allah ya yi musu da haninsa sai a alƙiyama ya yi musu babbar sakayya su riƙa kwasar ni'imar da ya ba su ta gidan Aljanna.

4. Falalar sallar dare da halaccin sallatar mafi yawancinsa.

5. Karancin bacci domin ɗa'a ga Allah ba abu ne mai cutar da jiki ba, domin Allah ba zai yi umarni da abin da zai cutar da bayinsa ba, har ma ya riƙa yabon masu aikata shi.

6. Bai halatta ga bawa ya ruɗu da kyawawan ayyukansa ba. Yana da kyau koyaushe ya riƙa ganin gazawarsa yana neman gafarar Allah.

7. Ayoyin da suke nuna samuwar Allah da Kaɗaitakarsa suna da yawa, ana kuma iya ganin su a cikin komai.

8. Babu wanda ya isa ya hana wa wani arzukinsa da Allah ya ƙaddara masa, domin kuwa yana zo masa ne ta inda babu mai iya hana shi. Don haka bawa sai ya nutsu ya nema a wurin Allah.

Suratuz Zariyat (15-23)

إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٍ ۝١٥ ءَاخِذِينَ مَآ ءَاتَىٰهُمۡ رَبُّهُمۡۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَبۡلَ ذَٰلِكَ مُحۡسِنِينَ ۝١٦ كَانُواْ قَلِيلٗا مِّنَ ٱلَّيۡلِ مَا يَهۡجَعُونَ ۝١٧ وَبِٱلۡأَسۡحَارِ هُمۡ يَسۡتَغۡفِرُونَ ۝١٨ وَفِيٓ أَمۡوَٰلِهِمۡ حَقّٞ لِّلسَّآئِلِ وَٱلۡمَحۡرُومِ ۝١٩ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ ءَايَٰتٞ لِّلۡمُوقِنِينَ ۝٢٠ وَفِيٓ أَنفُسِكُمۡۚ أَفَلَا تُبۡصِرُونَ ۝٢١ وَفِي ٱلسَّمَآءِ رِزۡقُكُمۡ وَمَا تُوعَدُونَ ۝٢٢ فَوَرَبِّ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ إِنَّهُۥ لَحَقّٞ مِّثۡلَ مَآ أَنَّكُمۡ تَنطِقُونَ ۝٢٣

15. Lalle masu taƙawa suna cikin gidajen Aljanna da idanuwan (ruwa).

16. Suna masu kwasar abin da Ubangijinsu Ya ba su. Lalle su sun zamanto kafin wannan (ranar) masu kyautata ayyuka ne.

17. Sun kasance kaɗan ne na dare suke bacci.

18. A gefin asuba kuma su suna neman gafara.

19. A cikin dukiyoyinsu kuma akwai wani haƙƙi na mai bara da mai kamewa daga yin ta.

20. A cikin ƙasa kuma akwai ayoyi ga masu sakankancewa.

21. Da kuma cikin kawunanku. Yanzu ba kwa lura ba?

22. A cikin sammai kuma akwai arzikinku da kuma abin da aka yi muku alkawarinsa.

23. To na rantse da Ubangijin sammai da ƙasa, lalle shi (abin da ake yi muku gargaɗinsa) tabbas gaskiya ne kamar dai yadda kuke yin magana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci masu kiyaye dokokinsa da bin umarninsa da guje wa haninsa, ya bayyana gwaggwaɓan sakamakonsu a ranar alƙiyama inda zai saka musu da gidajen Aljanna waɗanda idanuwan ruwa suke gudana a cikinsu. Za su riƙa kwasar ni'imomin da ya ba su a Aljanna suna masu gamsuwa da su, domin sun ƙasance tun a duniya masu kyautata ibadarsu ne ga Allah, suna bauta masa kamar suna ganin sa, sun kuma tabbatar idan ba sa ganin sa to shi yana ganin su, suna kuma kyautata wa bayinsa da duk wani nau'i na kyautatawa.

Daga cikin kyautata ibadarsu ga Allah kuwa sun ƙasance masu yawaita sallolin dare ne, ba sa yin bacci sai ɗan lokaci ƙanƙani, da zarar kuma sun fuskanci asuba ta kawo kai sai su shiga yin istigfari suna neman gafarar Allah game da laifukansu da kasawarsu.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Salam (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya ku mutane, ku yaɗa sallama, kuma ku ciyar da abinci, ku kuma sa da zumunci, ku yi salla cikin dare yayin da mutane suke bacci, za ku shiga Aljanna da aminci." [Tirmizi #2485 da Darimi #1501 da Ibn Majah #1334].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda waɗannan bayi nasa masu taƙawa suke kyautata wa bayinsa, domin sun san cewa a cikin dukiyoyinsu akwai wani haƙƙi da suke fitarwa don su ba wa mabuƙata, mai bara daga cikinsu ko mai kamewa ba ya roƙon kowa duk kuwa da buƙatarsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ayoyinsa na sama da na ƙasa masu tabbatar da cikar Kudurarsa da ikonsa. Waɗannan ayoyi kuwa su ne, waɗancan bayin nasa koyaushe suke la'akari da su suna ƙara musu yaƙini da sakankancewa da alƙawarin Allah.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a ƙasa da abubuwan da ta ƙunsa na duwatsu da koguna da ƙoramu da bishiyoyi da tsirrai da dabbobi da sauransu, dukkansu akwai ƙwararan ayoyi masu nuna girman Kudurar Allah da tabbatar da cewa, shi ne mahaliccin da ya ƙagi duk wata halitta. Wannan yana ƙara wa bayinsa nagari yaƙini. Hakanan ya bayyana cewa, a tare da halittar mutane su kansu akwai ayoyi masu ɗimbin yawa da suke tabbatar da Kaɗaitakarsa da Kudurarsa, don haka ya ja hankalin mutane da cewa, me ya sa ba sa lura ne su gani don su ɗau izina?

Ya kuma bayyana cewa, a cikin sama akwai arzikin da ya tanadar wa halittunsa, arzuki na duniya da na addini, domin daga nan ne ake saukar da sinadarin samun kowane arziki na duniya, watau ruwan sama; daga nan ne kuma wahayi wanda shi ne arziki na addini yake saukowa ta hanyar mala'ika. Hakanan daga sama ne abin da ake yi musu alƙawarinsa na alheri ko na sharri yake saukowa.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da Zatinsa; watau zamantowarsa Ubangijin sama da ƙasa don ya tabbatar da cewa, tashi bayan mutuwa gaskiya ne babu kokwanto a cikinsa, kamar yadda mutane ba sa kokwanton maganar da ke fitowa daga bakunansu.

Daga wadannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin hikimar Allah da yake ba wa bayinsa labaran mutanen kirki da na banza, domin su ɗauki wa'azi da izina daga gare su.

2. Girman darajar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe labarinsa da jan hankalin Manzonsa, don nuna masa muhimmancinsa.

3. Karrama baƙo abu ne mai matuƙar kyau, kuma sunnar Annabi Ibrahimu ce wadda Allah ya yabe shi a kanta.

4. Ana son karrama baƙo da duk wani nau'in karramawa ta hanyar magana ko aiki.

5. Da alama gidan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wuri ne na saukar baƙi daga ko'ina, domin da zuwansu kawai shiga suka yi, sannan suka yi sallama shi kuma ya yi musu kyakkyawar amsa.

6. Gaggauta gabatar wa da baƙo abin karramawa a gare shi ba tare da jinkiri ba ko buƙatar tambayarsa.

7. Wadatar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da yawan karamcinsa, dubi yadda ya kawo wa baƙinsa gasasshen ɗan maraƙi mai mai sukutum lokaci ɗaya.

8. Tsananin karamcin Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), dubi yadda ya riƙa hidimta wa baƙinsa da kansa duk da girman matsayinsa a wurin Allah da yawan shekarunsa.

9. Amfani da harshe mai taushi wanda yake cike da girmamawa yayin gabatar da kaɓakin abinci.

10. Duk wanda ya riƙa nuna jin tsoransa ga wani mutum saboda wani dalili, to wajibi ne ga wanda ake jin tsoron ya yi abin da zai cire masa wannan tsoron daga zuciyarsa, domin ya sami nutsuwa da shi ya amince masa.

11. Annabawa su ma sukan ji tsoro irin na ɗabi'a, wannan kuwa ba abu ne da zai rage matsayinsu ba.

12. Mala'iku sukan rikiɗa a surar mutane don isar da wani saƙo na Allah.

13. Yi wa ɗan'uwanka albishir na wani alheri da zai samu abu ne mai kyau.

14. Haihuwa baiwa ce daga Allah, yakan ba da ita ga wanda ya ga dama ko da kuwa ya kai wasu shekaru har ya yanke ƙauna ko kuma ya kasance bakarare ne wanda ba ya haihuwa.

Suratuz Zariyat (24-30)

هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ضَيۡفِ إِبۡرَٰهِيمَ ٱلۡمُكۡرَمِينَ ٢٤ إِذۡ دَخَلُواْ عَلَيۡهِ فَقَالُواْ سَلَٰمٗاۖ قَالَ سَلَٰمٞ قَوۡمٞ مُّنكَرُونَ ٢٥ فَرَاغَ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِۦ فَجَآءَ بِعِجۡلٖ سَمِينٖ ٢٦ فَقَرَّبَهُۥٓ إِلَيۡهِمۡ قَالَ أَلَا تَأۡكُلُونَ ٢٧ فَأَوۡجَسَ مِنۡهُمۡ خِيفَةٗۖ قَالُواْ لَا تَخَفۡۖ وَبَشَّرُوهُ بِغُلَٰمٍ عَلِيمٖ ٢٨ فَأَقۡبَلَتِ ٱمۡرَأَتُهُۥ فِي صَرَّةٖ فَصَكَّتۡ وَجۡهَهَا وَقَالَتۡ عَجُوزٌ عَقِيمٞ ٢٩ قَالُواْ كَذَٰلِكِ قَالَ رَبُّكِۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡحَكِيمُ ٱلۡعَلِيمُ ٣٠

24. Shin labarin baƙin Ibrahimu masu girma ya zo maka?

25. Lokacin da suka shiga wurinsa sai suka ce: "Muna maka sallama;" ya ce: "Aminci ya tabbata gare ku, (ku) mutane ne da ba sanannu ba."

26. Sai ya saɗaɗa da sauri zuwa ga iyalinsa, sai ya zo da wani ɗan maraƙi mai mai.

27. Sai ya kusanta shi gare su, ya ce: “Yanzu ba za ku ci ba?”

28. (Da suka ƙi ci) sai ya tsorata da su, suka ce: “Kada ka tsorata;” suka kuma yi masa albishir da samun yaro mai ilimi.

29. Sannan sai matarsa ta gabato su cikin wata ƙara, sai ta mari fuskarta ta ce: “Yanzu tsohuwa bakarara (ita ce za ta haihu?)”

30. Suka ce, “Kamar haka Ubangijinki Ya ce, lalle Shi Mai hikima ne, Masani.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Annabinsa Muhammadu (ﷺ) labarin wasu baƙin mala’iku waɗanda suka zo wa Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a siffar mutane, ya kuma karrama su.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin da suka isa gidan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun yi masa sallama bayan sun shiga, shi kuma ya mayar musu da mafi kyan sallama, to amma sai a ransa ya ce: Waɗannan mutane ne da ba mu san su ba. Sai ya saɗaɗa a ɓoye da sauri zuwa ga iyalansa ya zo musu da wani gasasshen ɗan maraƙi mai mai, yana zaton su mutane ne. Sai ya kusantar da gasasshen ɗan marakin gare su yana yi musu tayin su ci tare da tambayar su ko ba za su ci ba ne? Yayin da ya kula hannnayensu ba sa isa wurin wannan abincin sai ya tsorata da su, sai su kuma da suka kula da ya tsorata da su sai suka kwantar masa da hankali da cewa, kada ya ji tsoro; su mala’iku ne, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko su don su hallaka mutanen Annabi Luɗu waɗanda suka ƙi yin imani da shi. Sannan suka yi masa albishir da samun ɗa mai ilimi, watau Annabi Is’haƙa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Matarsa Saratu tana jin wannan albishir sai ta nufo su da sauri tana sowa, saboda farin ciki, har tana marin kanta, tana cewa, ita fa tsohuwa ce kuma bakarara ba ta haihuwa, to ta yaya za ta sami ɗa, ga shi shekarunta da na mijinta Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ja sosai?

Sai mala’ikun nan suka tabbatar mata da cewa, kamar haka dai Ubangijinta Allah ya ƙaddara, don haka babu abin da zai hana faruwarsa, domin shi mai hikima ne cikin duk halittarsa, mai kuma cikakken ilimi ne, ya san duk wani abu da ya shafi halittunsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin karrama baƙo kada a fara tambayar sa abin da yake tafe da shi har sai an gama ba shi liyafa tukun, domin kada gaggauta tambayar ta sa shi ya zaci ko ana alla-alla ne ya tafi ba a buƙatar kasancewarsa a gidan.

2. Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan ya fahimci cewa, baƙin nan nasa mala’iku ne, sai ya gane cewa saukarsu a cikin kamannin da ya gan su ba zai zama don yi masa albishir ne don samun haihuwa kaɗai ba, lalle akwai wani babban al’amari da ke tafe da su, wannan ya sanya shi ya tambaye su abin da yake tafe da su.

3. Lalle aikin mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) babban laifi ne wanda ya cancanci uƙuba mai tsananin gaske.

4. Bayanin tserar da muminai da hallaka kafirai.

5. Mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) gaba ɗayansu ba su yi imani da shi ba.

6. Babu masu wa’azantuwa da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sai masu jin tsoron sa.

Suratuz Zariyat (31-37)

۞قَالَ فَمَا خَطۡبُكُمۡ أَيُّهَا ٱلۡمُرۡسَلُونَ ٣١ قَالُوٓاْ إِنَّآ أُرۡسِلۡنَآ إِلَىٰ قَوۡمٖ مُّجۡرِمِينَ ٣٢ لِنُرۡسِلَ عَلَيۡهِمۡ حِجَارَةٗ مِّن طِينٖ ٣٣ مُّسَوَّمَةً عِندَ رَبِّكَ لِلۡمُسۡرِفِينَ ٣٤ فَأَخۡرَجۡنَا مَن كَانَ فِيهَا مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٣٥ فَمَا وَجَدۡنَا فِيهَا غَيۡرَ بَيۡتٖ مِّنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ٣٦ وَتَرَكۡنَا فِيهَآ ءَايَةٗ لِّلَّذِينَ يَخَافُونَ ٱلۡعَذَابَ ٱلۡأَلِيمَ ٣٧

31. (Ibrahimu) ya ce: “To me yake tafe da ku, ya ku waɗannan manzanni?”

32. Suka ce: “Lalle mu an aiko mu ne zuwa ga wasu mutane masu manyan laifuka.

33. “Don mu zuba musu ƙonannun duwatsu na taƀon (wuta).

34. “Waɗanda aka yi wa alama daga wurin Ubangijinka saboda maƀarnata.”

35. Sai Muka tserar da duk wanda ya kasance a cikinta (alƙaryar) daga muminai.

36. Sai ba mu sami wani (gida) a cikinta ba in ban da gida ɗaya na Musulmi.

37. Muka kuma bar aya ta wa’azi a cikinta ga waɗanda suke tsoron azaba mai raɗaɗi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fahimci cewa waɗannan fa ba mutane ne ba, mala’iku ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko su, sai ya tambaye su, me yake tafe da su? Sai suka amsa masa da cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko su ne zuwa ga wasu mutane masu miyagun laifuka, watau mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), domin su sakar musu daskararren taƀo na wuta, wanda aka yi wa alama daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) domin hallaka mutanen da suka wuce iyaka wajen aikata laifuka.

To a nan ne Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiga jayayya da su don yana son a janye musu wannan azabar, amma aka faɗa masa cewa, ya fita daga wannan maganar, al’amarin Allah ya riga ya zo, babu abin da zai tsai da shi.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fitar da duk wani mumini daga cikin wannan gari na Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don kada wannan azaba ta shafe su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya fita shi da ilahirin iyalan gidansa cikin dare, matarsa ce kaɗai wadda ba za ta kai labari ba, domin ita tana cikin waɗanda za su hallaka saboda kafircinta. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, gida ɗaya ne kawai na Musulmi aka samu a wannan gari, shi ne gidan Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sauran gidajen duk Allah ya hallaka su.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya bar aya ta wa’azi na guraben azabar da ta sauko wa wannan garin, domin ya zama abin izina ga waɗanda suke jin tsoron azaba mai raɗaɗi, don su guji aikata irin waɗannan munanan ayyuka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A koyaushe a tsawon tarihi azzaluman shugabanni sukan yi tinƙaho ne da ƙarfin rundunoninsu har suke ƙaryata gaskiya suna faɗa da masu kawo gyara.

2. Jifar masu kawo gyara cikin al’umma da tuhumce-tuhumce na ƙarya da kiran su da miyagun sunaye, daɗaɗɗiyar al'ada ce ta manyan azzalumai a tarihin ɗan’adam.

3. Mummunan ƙarshe ga duk wasu azzalumai da mataimakansu da rundunoninsu gaba ɗaya.

Suratuz Zariyat (38-40)

وَفِي مُوسَىٰٓ إِذۡ أَرۡسَلۡنَٰهُ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ بِسُلۡطَٰنٖ مُّبِينٖ ٣٨ فَتَوَلَّىٰ بِرُكۡنِهِۦ وَقَالَ سَٰحِرٌ أَوۡ مَجۡنُونٞ ٣٩ فَأَخَذۡنَٰهُ وَجُنُودَهُۥ فَنَبَذۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡيَمِّ وَهُوَ مُلِيمٞ ٤٠

38. Game da Musa kuma (akwai aya), lokacin da Muka aiko shi zuwa ga Fir’auna da hujjoji bayyanannu.

39. Sai ya ba da baya shi da ƙarfin rundunarsa, ya kuma ce: “(Musa) mai sihiri ne ko mahaukaci.”

40. Saboda haka Muka kama shi tare da rundunarsa, sai Muka watsa su a cikin kogi, alhali yana mai aikata abin Allah-wadai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya aika Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga Fir’auna da hujjoji bayyanannu waɗanda suke tabbatar da gaskiyar manzancinsa, kamar sandarsa da hannunsa mai haske, to amma sai Fir’auna ya bijire wa gaskiya ya ƙaryata Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya riƙa tinƙaho da ƙarfin mulkinsa da rundunarsa, ya ƙi ya ɗauki darasi daga al’ummun baya da Allah ya hallaka. Ya shiga tuhumar Annabi Musa da cewa shi matsafi ne kawai da yake ruɗar mutane da tsafinsa, ko kuma ma mai taɓin hankali ne bai san abin da yake faɗa ba.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya damƙi Fir’auna shi da rundunarsa gaba ɗaya ya nutsar da su a cikin ruwa duk suka hallaka alhalin Fir’auna ya zo da abin Allah-wadai, abin assha, watau da’awar allantaka da ƙaryata Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana hallaka wanda ya so ya hallaka shi da duk abin da ya so ko da kuwa abin a zahirinsa ni’ima ce, kamar yadda ya hallaka Adawa da iska.

2. Jan hankali ga mushirikan Larabawa a kan su shiga taitayinsu, domin a baya can Allah ya hallaka al’ummun da suka fi su ƙarfi da yawa, don haka su ma ba za su gagare shi ba.

3. Haɗarin girman kai da take gaskiya, domin shi ne ya jawo wa Samudawa hallaka.

Suratuz Zariyat (41-46)

وَفِي عَادٍ إِذۡ أَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمُ ٱلرِّيحَ ٱلۡعَقِيمَ ٤١ مَا تَذَرُ مِن شَيۡءٍ أَتَتۡ عَلَيۡهِ إِلَّا جَعَلَتۡهُ كَٱلرَّمِيمِ ٤٢ وَفِي ثَمُودَ إِذۡ قِيلَ لَهُمۡ تَمَتَّعُواْ حَتَّىٰ حِينٖ ٤٣ فَعَتَوۡاْ عَنۡ أَمۡرِ رَبِّهِمۡ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلصَّٰعِقَةُ وَهُمۡ يَنظُرُونَ ٤٤ فَمَا ٱسۡتَطَٰعُواْ مِن قِيَامٖ وَمَا كَانُواْ مُنتَصِرِينَ ٤٥ وَقَوۡمَ نُوحٖ مِّن قَبۡلُۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَوۡمٗا فَٰسِقِينَ ٤٦

41. Kuma game da Adawa (akwai aya), lokacin da Muka aiko musu da iska marar alhairi.

42. Ba ta barin wani abu idan ta biyo ta kansa sai ta mayar da shi kamar daddagagge ƙashi.

43. Kuma game da Samudawa (akwai aya), lokacin da aka ce da su: “Ku ji daɗi zuwa wani ɗan lokaci.”

44. Sai suka yi tsaurin kai game da umarnin Ubangijinsu, saboda haka tsawa ta faɗa musu alhali kuwa suna kallo.

45. To ba su sami damar tsayuwa ba, kuma ba su zamanto masu taimaka wa (junansu) ba.

46. Kuma (Mun hallakar da) mutanen Nuhu a gabaninsu; don kuwa lalle sun kasance mutane ne fasiƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da kawo ƙissoshin al'ummun da suka gabata waɗanda ya hallaka su yayin da suka ƙaryata annabawansu, don hakan ya zama aya ga masu jin tsoron azabarsa mai raɗaɗi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci labarin Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka ƙaryata Manzonsu Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu wata bakarara iska wadda babu alheri a cikinta ko kaɗan wadda ba abin da za ta biyo ta kansa na mutum ko dabba ko dukiya sai ta yi rugurugu da shi ta mayar da shi kamar daddagaggen ƙashi.

Sannan da Samudawa waɗanda suka ƙaryata Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka cutar da taguwarsa bayan an ja musu kunne, don haka su ma aka ba su wa'adin kwana uku su ji daɗin rayuwarsu a cikinsu aka hallaka su.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, sun yi tsaurin kai game da umarnin Ubangijinsu suka ƙi yin imani da yi wa Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) biyayya, saboda haka azabar tsawa ta auka musu suna kallo amma ba yadda za su iya kauce mata har suka hallaka gaba ɗayansu.

Sai kuma mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda sun gabaci Adawa da Samudawa, su ma sun ƙaryata Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), don haka Allah ya dulmiyar da su a ruwa, domin sun tabbata mutane ne fasiƙai da suke bijire wa Allah da Manzonsa Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da Kaɗaitakar Allah da Uluhiyyarsa ta hanyar duba cikin halittunsa na sama da na ƙasa.

2. Alƙur'ani shi ne littafin da tun ɗaruruwan shekaru ya tabbatar da batun cewa, kowane abu a duniya, a sama ko a ƙasa, Allah ya halicce su nau'i bibbiyu ne, tun gabanin wani ilimi na zamani ya gano haka.

Suratuz Zariyat (47-49)

وَٱلسَّمَآءَ بَنَيۡنَٰهَا بِأَيۡيْدٖ وَإِنَّا لَمُوسِعُونَ ۝٤٧ وَٱلۡأَرۡضَ فَرَشۡنَٰهَا فَنِعۡمَ ٱلۡمَٰهِدُونَ ۝٤٨ وَمِن كُلِّ شَيۡءٍ خَلَقۡنَا زَوۡجَيۡنِ لَعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ ۝٤٩

47. Sama kuma Mun gina ta da ƙarfi, lalle kuma Mu tabbas Masu yalwatawa ne.

48. Kasa kuma Muka shimfiɗa ta, to madalla da Masu shimfiɗar.

49. Daga kowane abu kuma Mun halicci nau'i biyu, don ku wa'azantu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu manyan ayoyi guda uku waɗanda suke tabbatar da samuwarsa da Kaɗaitakarsa.

Ta farko, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, shi ne ya gina sama ya kuma inganta gininta da ƙarfin ikonsa ta zama kamar rufi ga ƙasa da abin da yake kanta. Sannan ya tabbatar da cewa, shi ne mai yalwatawa; yana yalwata sassan sammai da duk halittun da suke cikinsu da arziki wanda yake wadatacce.

Ta biyu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, shi ne ya shimfiɗa ƙasa domin halittunsa su ji daɗin rayuwa a kanta, ta zame musu kamar shimfiɗa. Sai ya yabi kansa da cewa 'madalla da masu shimfiɗar', watau yana nufin shi kansa.

Aya ta uku, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya halicci kowane abu nau'i bibbiyu, kamar namiji da mace da sama da ƙasa da tudun ƙasa da ruwa, ya yi haka ne kuma don mutane su wa'azantu, su faɗaku da ganin ni'imomin Allah daban-daban waɗanda suke nuna cikar Kudurarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoron Allah na gaske yana nufin gudu da komawa zuwa gare shi ta hanyar kyawawan ayyuka da guje wa duk wani laifi na sarari da na ɓoye. Mutum ya guje wa kafirci zuwa imani; ya guje wa saɓon Allah zuwa ɗa'a gare shi; ya guje wa jahilci zuwa ilimi; ya guje wa rafkana zuwa ga zikirin Allah da tuna shi koyaushe. Duk wanda ya yi haka to lalle ya cika addininsa, ya guje wa duk wani abin ban tsoro da abin ƙi, ya kuma sami biyan buƙatarsa.

2. Babbar komawa kan hanyar Allah shi ne guje wa shirka da bautar wanin Allah.

3. Annabi Muhammadu (ﷺ) ya isar wa al'ummarsa saƙon Allah a sarari bai ɓoye musu komai ba.

Suratuz Zariyat (50-51)

فَفِرُّوٓاْ إِلَى ٱللَّهِۖ إِنِّي لَكُم مِّنۡهُ نَذِيرٞ مُّبِينٞ ٥٠ وَلَا تَجۡعَلُواْ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَۖ إِنِّي لَكُم مِّنۡهُ نَذِيرٞ مُّبِينٞ ٥١

50. To ku gudo zuwa ga Allah, lalle ni mai gargaɗi ne game da Shi, mai bayyana (gargaɗi).

51. Kada kuma ku sanya wani abin bauta tare da Allah; lalle ni mai gargaɗi ne game da Shi, mai bayyana (gargaɗi)

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa da su gudu zuwa gare shi, watau su guje wa azabarsa zuwa ga kyakkyawan sakamakonsa ta hanyar komawa gare shi da yi masa biyayya da guje wa saɓa masa. Sannan ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya faɗa wa mutane cewa shi mai gargaɗi ne mai bayyana gargaɗinsa gare su don su guje wa uƙubar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Sai kuma ya bayyana musu babban abin da za su yi na komawa zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne su guji riƙon duk wani abin bauta ba Allah ba; ya sake tabbatar musu cewa, shi fa mai gargaɗi ne mai bayyana gargaɗinsa gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin Manzon Allah (ﷺ) game da muzgunawar da mushirikai suke yi masa da cewa ba shi ne farau ba; al'ummun da suka gabata sun yi wa annabawansu irin wannan cin mutumcin, amma suka yi haƙuri har Allah ya ba su nasara.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, kafiran farko da na ƙarshe sun yi kamanceceniya da juna wajen kafirci da ɗagawa, shi ya sa maganganunsu ma da ayyukansu suka yi kama da juna matuƙa kai ka ce wasiyya ce suka riƙa yi wa junansu.

3. Abin da aka ɗora wa mai wa’azi shi ne kawai ya yi wa’azi ya tunatar, amma shiriya ba a hannunsa take ba, tana a hannun Allah.

4. Tunatarwa iri biyu ce:

Ta farko, tunatar da mutane abin da sun riga sun san shi a dunƙule da hankulansu, sai a sanar da su shi dalla-dalla tare da nuna musu abin da yake cikinsa na alheri da maslaha. Duk wani umarni da hani a shari’a to yana daga cikin tunatarwa.

Ta biyu, tunatar da muminai abin da suka riga suka sani, to amma sun manta ko sun rafkana, to sai a tunatar da su, ta hanayar a yi ta maimaita musu shi har sai ya zauna a ƙwaƙwalansu, su kuma riƙa aiki da shi, yin haka zai ƙara musu karsashi da himma, sai su amfana da wannan tunatarwar.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, tunatarwa tana amfanar muminai, domin imani da ke tare da su da tsoron Allah da neman yardarsa ne zai sa duk wata tunatarwa da wa’azi su yi musu amfani. Amma mutumin da ba shi da imani to ba a shirye yake ya karɓi tunatarwa ko wa’azi ba.

Suratuz Zariyat (52-55)

كَذَٰلِكَ مَآ أَتَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا قَالُواْ سَاحِرٌ أَوۡ مَجۡنُونٌ ۝٥٢ أَتَوَاصَوۡاْ بِهِۦۚ بَلۡ هُمۡ قَوۡمٌ طَاغُونَ ۝٥٣ فَتَوَلَّ عَنۡهُمۡ فَمَآ أَنتَ بِمَلُومٖ ۝٥٤
وَذَكِّرۡ فَإِنَّ ٱلذِّكۡرَىٰ تَنفَعُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ۝٥٥

52. Kamar haka abin yake, ba waɗanda wani manzo ya zo musu a gabaninsu (mutan Makka) sai sun ce mai sihiri ne ko mahaukaci.

53. Shin wasiyya suke yi wa junansu ne game da shi? A’a, su dai mutane ne masu ƙetare iyaka.

54. Sai ka rabu da su, don kuwa kai ba abin zargi ba ne.

55. Kuma ka yi wa’azi, don ko lalle wa’azi yana amfanar muminai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mushirkan Makka da suke ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) ba su ne farau ba. Irin wannan ƙaryatawar waɗanda suka gabace su ma sun ƙaryata annabawansu, domin duk sa’adda wani manzo ya zo musu daga Allah sai su ce shi mai sihiri ne ko mahaukaci.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su cewa, shin wannan ƙazafi da suke yi wa manzannin Allah wai wata wasiyya ce suka yi wa junansu, watau na farko suka yi wa na baya? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ba wata wasiyya a tsakaninsu, su dai kawai mutane ne masu ɗagawa da ƙetare iyaka. Watau dukkansu ɗagawarsu ta sanya su ƙaryata manzannin Allah da yi musu ƙazafi.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da cewa ya rabu da su, ya kawar da kansa daga duk wani izgilinsu, shi dai ya isar musu da saƙon da aka aiko shi da shi, don haka shi ba wanda za a zarge shi ne da ɓoye saƙon da aka aiko shi da shi ba.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna masa cewa kawar musu da kai ba ya nufin ya daina yi musu wa’azi, a’a, ya ci gaba da yin wa’azinsa da tunatarwa domin lalle wa’azi yana amfanar muminai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babbar manufar halittar aljannu da mutane ita ce bautar Allah shi kaɗai ba tare da sanya masa wani abokin tarayya ba. Saboda wannan babbar manufa ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko da manzanni ya kuma saukar da littattafai, ya halicci Aljanna da wuta, ya shar'anta jihadi, ya raba mutane gida biyu, wasu masoyansa wasu kuma maƙiyansa, ya yi wa masoyansa alƙawarin kyakkyawan sakamako duniya da lahira, ya kuma tanadar wa maƙiyansa azabar wulaƙanci a duniya da lahira.

2. Cikakkiyar wadatuwar Allah daga bayinsa. Ana bauta wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne ba don buƙatar kansa ba sai don buƙatar mai bautar a wurinsa, don haka wanda bai bauta masa ba shi ne ya yi hasara ya cuci kansa, domin bai cuci Allah da komai ba.

3. Arziki duka yana hannun Allah, shi ne yake arzuta kowa da komai, babu mai ba da arzuki ko ya riƙe shi sai dai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Allah ne mai tsananin ƙarfi mai cikakkiyar Kudura wanda ya halicci dukkan halittu na sama da na ƙasa, shi ne kuma mai ikon sarrafa su yadda ya ga dama, babu abin da yake gagarar sa.

5. Sunnar Allah guda ɗaya ce a kan duk wani mai ƙaryata manzannin Allah, ya yi masa tanadin azaba da babu makawa sai ta auka masa matuƙar bai tuba ya koma ga Allah ba.

Suratuz Zariyat (56-60)

وَمَا خَلَقْتُ ٱلْجِنَّ وَٱلْإِنسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ ﴿٥٦﴾ مَآ أُرِيدُ مِنْهُم مِّن رِّزْقٍ وَمَآ أُرِيدُ أَن يُطْعِمُونِ ﴿٥٧﴾ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلرَّزَّاقُ ذُو ٱلْقُوَّةِ ٱلْمَتِينُ ﴿٥٨﴾ فَإِنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ ذَنُوبًا مِّثْلَ ذَنُوبِ أَصْحَٰبِهِمْ فَلَا يَسْتَعْجِلُونِ ﴿٥٩﴾ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن يَوْمِهِمُ ٱلَّذِى يُوعَدُونَ ﴿٦٠﴾

56. Ban halicci mutum da aljan ba sai don su bauta min.

57. Ba Na neman wani arziki a wurinsu, kuma ba Na neman su ciyar da Ni.

58. Lalle Allah Shi ne Mai arzutawa, Mai tsananin ƙarfi.

59. To lalle waɗanda suka zalunci (kansu) suna da wani kaso na azaba kamar kason abokansu, saboda haka kada su nemi gaggauto shi.

60. To tsananin azaba ya tabbata ga waɗanda suka kafirta a ranar da ake alƙawarta musu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana babbar manufar halittar mutane da aljannu, watau shi ne su bauta masa kada su haɗa komai da shi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba ya neman wani arziki daga halittarsa, kuma ba ya neman su ciyar da shi, domin shi mawadaci ne ta kowace fuska; mutane da aljannu da duk sauran halittu su ne suke da buƙata a wurinsa, don haka shi ne mai arzuta bayinsa kuma mai tsananin ƙarfi wadda babu mai iya ja da shi, mutum da aljan duka dole su rusuna wa ƙarfinsa.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda suka ƙaryata Manzonsa (ﷺ) sun zalunci kansu da kansu, kuma su sani tabbas za su ɗanɗani kuɗarsu, domin suna da kasonsu na azaba da aka tanadar musu irin yadda aka tanadar wa kafiran farko nasu kasonsu na azaba; to su daina neman a gaggauto musu da shi wai don suna zaton ƙarya ne, su sani yana da ƙayyadadden lokaci da Allah ya ajiye masa; idan lokacinsa ya zo babu mai iya kuɓutar da su, don haka tsananin azaba ya tabbata ga mutanen

da suka kafirce wa Allah, kuma suka ƙaryata Manzonsa a ranar alƙiyama wadda ake yi musu alƙawarin zuwanta

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da waɗannan manyan abubuwa, domin jan hankali zuwa ga girman sha'aninsu da babbar hikimar Allah da take tattare da su.

2. Wasu malamai sun fassara 'rubutaccen Littafi' da cewa ana nufin Attaura da Allah ya ba wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Suka ce hikimar ambatonta a nan shi ne, kasancewar ita ce littafin da ake da shi a lokacin wanda ya soki lamarin shirka ƙarara kamar yadda Alƙur'ani ya yi, don nuna musu ba Alƙur'ani ne farau ba wajen sukan lamarin shirka, domin littafin Attaura ya riga shi sauka.

3. Ambaton girgizar sama da gushewar duwatsu daga inda suke yana nufin sanar da cewa rayuwar duniya ta zo ƙarshe, domin samuwar sama da ƙasa da duwatsun da ke tsakaninsu da tekuna da ƙoramu dukkansu Allah ya aje su ne domin hidimta wa rayuwar ɗan'adam a bayan ƙasa. Don haka idan sun gushe to rayuwarsa a duniya ma ta ƙare babu dawowa a cikinta nan gaba.

4. Tabbatar da ranar alƙiyama da sakamako mai daɗi da marar daɗi

52-Suratuɗ Ɗur

Mabuɗin Surar:

1. Sunanta:
Sunanta '*Suratuɗ Ɗur*' kamar yadda ya zo a cikin littattafan hadisi da na tafsiri da mus'hafai. [Dubi, Bukhari #464 da 4854 da Muslim #1276].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a kan cewa ita Sura ce *Makkiyya*, watau an saukar da ita kafin hijira zuwa Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta saba'in da biyar (75) a jerin saukar surorin Alƙur'ani; ta sauka bayan '*Suratu Nuh*' gabanin '*Suratul Mu'uminun*'.

4. Adadin Ayoyinta:
A lissafin mutanen Sham da Kufa ayoyinta arba'in da tara ne (49), amma a lissafin mutanen Basra arba'in da takwas ne (48), a lissafin mutanen Makka da Madina kuwa arba'in da bakwai ne (47).

5. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Surar shi ne rushe du wani ruɗami na masu karyata Manzon Allah (ﷺ) a kan gaskiyar da ya zo musu da ita, ta hanyar kawo ƙarfafan hujjoji da dalilai waɗanda za su sa dole mutum ya rusuna ya miƙa wuya.

6. Daga Cikin Abubuwa Da Ta Kunsa Akwai:
• Tsoratar da mushirikai masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da azabar Allah a gare su ranar alƙiyama.
• Alƙawarin samun ni'imar Allah ga muminai masu taƙawa da bayanin yadda suke jin tsoron Allah suna yabon sa da ambaton ni'imar da ya yi musu.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) game da munanan maganganu da kafirai suke faɗa masa.
• Kalubalantar Larabawa da su kawo wani abu kamar Alƙur'ani.
• Rushe ra'ayoyin mushirikai na ƙaryata dawo da matattu da aiko da wani manzo wanda ba ɗaya ne daga cikin manyansu ba, da da'awar cewa mala'iku 'ya'yan Allah ne mata.
• Rushe aƙidarsu ta samuwar alloli barkatai.
• Umarni ga Manzo (ﷺ) da ya yi watsi da mushirikai, ya kuma yi haƙuri da su, kada ya yi baƙin ciki game da duk sharrin da suke ƙulla masa, domin narkon Allah na azaba zai sauka a kansu a duniya da lahira, don haka Allah yana tare da shi, sai ya ci gaba da gode masa.

Suratuɗ Ɗur (1-16)
وَٱلطُّورِ ۝١ وَكِتَٰبٍ مَّسۡطُورٖ ۝٢ فِي رَقّٖ مَّنشُورٖ ۝٣ وَٱلۡبَيۡتِ ٱلۡمَعۡمُورِ ۝٤ وَٱلسَّقۡفِ ٱلۡمَرۡفُوعِ ۝٥ وَٱلۡبَحۡرِ ٱلۡمَسۡجُورِ ۝٦ إِنَّ عَذَابَ رَبِّكَ لَوَٰقِعٞ ۝٧
مَّا لَهُۥ مِن دَافِعٖ ۝٨ يَوۡمَ تَمُورُ ٱلسَّمَآءُ مَوۡرٗا ۝٩ وَتَسِيرُ ٱلۡجِبَالُ سَيۡرٗا ۝١٠ فَوَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ۝١١ ٱلَّذِينَ هُمۡ فِي خَوۡضٖ يَلۡعَبُونَ ۝١٢ يَوۡمَ يُدَعُّونَ

إِلَىٰ نَارِ جَهَنَّمَ دَعًّا ﴿١٣﴾ هَٰذِهِ ٱلنَّارُ ٱلَّتِي كُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ﴿١٤﴾ أَفَسِحْرٌ هَٰذَآ أَمْ أَنتُمْ لَا تُبْصِرُونَ ﴿١٥﴾ ٱصْلَوْهَا فَٱصْبِرُوٓا۟ أَوْ لَا تَصْبِرُوا۟ سَوَآءٌ عَلَيْكُمْ ۖ إِنَّمَا تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿١٦﴾

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da dutsen Ɗuri.

2. Da kuma rubutaccen littafi.

3. Cikin buɗaɗɗiyar takardar fata.

4. Da kuma *Al-Baitul-Ma'amur*.

5. Da kuma rufi abin ɗaukakawa.

6. Da kuma kogi cikakke maƙil.

7. Lalle azabar Ubangijinka tabbas mai aukuwa ce.

8. Ba wani mai ingije ta.

9. A ranar da sama za ta yi matsananciyar jujjuyawa.

10. Duwatsu kuma su riƙa tafiya (suna barin wurarensu).

11. To tsananin azaba a wanan ranar ya tabbata ga masu ƙaryatawa.

12. Waɗanda suke wasanni cikin ɓarna.

13. A ranar da za a ingiza su zuwa ga wutar Jahannama ingizawa.

14. (Za a ce da su): "Wannan ita ce wutar da kuka kasance kuna ƙaryatawa.

15. "Yanzu sihiri ne wannan ko kuwa ku ne ba kwa gani?

16. "To ku shige ta, sai ku yi haƙuri ko kada ku yi haƙuri duk ɗaya ne; ana saka muku ne kawai da abin da kuka kasance kuna aikatawa."

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da rantsuwa da wasu manyan abubuwa guda biyar, su ne:
Na farko, ya rantse da dutsen Ɗuri, shi ne dutsen da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a gefensa, ya kuma ba shi littafin Attaura a nan wurin.
Na biyu, ya yi rantsuwa da rubutaccen littafi, wasu malamai sun ce ana nufin littafin Lauhul Mahfuzu wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rubuta komai a cikinsa. Wasu kuma sun ce shi ne littafin Attaura da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a rubuce

a cikin alluna. Wasu kuma suka ce shi ne duk wani littafi da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa manzanninsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta wannan littafin rubutacce da cewa, an rubuta shi a cikin fata mai taushi abar buɗewa.
Na uku, ya yi rantsuwa da *'Al-Baitul Ma'amur*', shi ne ɗakin da ke a sama ta bakwai, wanda a koyaushe mala'iku suke raya shi da bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "*Al-Baitul Ma'amuru* yana sama ta bakwai, kullum mala'iku dubu saba'in ne suke shiga cikinsa sannan ba za su sake komawa cikinsa ba har alƙiyama ta tashi." [Ahmad #12558 da Hakim #3742].
Ya zo a cikin dogon hadisin Isra'in Manzon Allah (ﷺ) da Mi'irajinsa wanda Malik ɗan Sa'asa'a (Allah ya ƙara masa yarda) ya ruwaito, Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "....Sannan aka ɗage min sai na ga *Al-Baitul Ma'amur*, sai na tambayi Jibrilu game da shi, sai ya ce mini: "Wannan ne *Baitul Ma'amur* , a kullum mala'ika dubu saba'in ne suke yin salla a cikinsa, idan sun fita dukkansu ba za su sake komowa cikinsa ba har abada." [Bukhari #3207 da Muslim #164].
Na huɗu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da sama abar ɗaukakawa kamar rufi ga ƙasa.
Na biyar, ya rantse da kogi wanda yake cike da ruwa maƙil, amma Allah ya hana shi ya yi ambaliya ya mamaye bayan ƙasa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin waɗannan rantse-rantse, watau shi ne tabbatar da aukuwar azabar Allah ga kafirai masu musunta tashin alƙiyama, masu jayayya da Manzon Allah (ﷺ). Idan kuma azabarsa ta auku to babu mai iya ture ta, domin babu mai iya ja da ikon Allah, babu kuma mai iya tsere masa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta ranar aukuwar wannan azaba, da cewa, ita ce ranar da sama za ta girgiza sosai, duwatsu kuma a gusar da su daga wurarensu su riƙa tashi sama bayan an niƙe su tilis sun zama kamar ƙura.Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, tsananin azaba a wannan ranar ya tabbata ga masu ƙaryata alƙawarin Allah da tashin alƙiyama. Waɗanda suka rayu a duniya cikin kutse a cikin ƙarya da ɓarna suna ta wasanninsu sun gafala daga tuna Allah da ranar alƙiyama. A ranar za a zo da su ana ingiza su cikin wutar Jahannama da ƙarfi, ana faɗa musu cikin izgili da zargi cewa, wannan ita ce wutar da suka kasance kuna ƙaryatawa a duk sanda manzanninsu suka yi muku wa'azi suka tsoratar da su ita. Ana kuma tambayar su cewa, to yanzu wannan ma da suke gani shi ma sihiri ne, ko kuma ma babu abin da idanunsu suke gane musu? Don haka sai a ci gaba da cewa su ɗanɗani azabar wuta, haƙurinsu da rashin haƙurinsu a yau duk ɗaya ne, domin babu abin da zai amfana musu, kuma munanan ayyukansu ne suka jawo musu wannan mummunan sakamakon, babu wanda ya zalunce su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Taƙawa, watau bin umarnin Allah da guje wa haninsa sababi ne na shiga gidan Aljanna.

2. Tsare muminai daga azabar wutar Jahannama wani adalci ne na Ubangiji domin ba su aikata abin da suka cancanci shiga wuta ba. Amma shigar da su gidan Aljanna wannan wata falala ce daga Allah a gare su.

3. Abincin 'yan Aljanna da abin shansu dukkansu lafiyayyu ne, ba sa ɗauke da wani abin cutarwa.

4. Kishingiɗa yayin cin abinci ko shan abin sha wani yanayi ne na waɗanda suke cikin more rayuwa, kamar yadda ake gani a nan duniya. Bayanin cewa gadajensu a jejjere suke yana nufin suna da yawa kuma an aje su a cikin kyakkyawan tsari mai ban sha'awa, kuma waɗanda suke kishingiɗa a kansu suna cike da farin ciki da juna.

Suratuɗ Ɗur (17-20)

إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَنَعِيمٖ ١٧ فَٰكِهِينَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمۡ رَبُّهُمۡ وَوَقَىٰهُمۡ رَبُّهُمۡ عَذَابَ ٱلۡجَحِيمِ ١٨ كُلُواْ وَٱشۡرَبُواْ هَنِيٓـَٔۢا بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ١٩ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ سُرُرٖ مَّصۡفُوفَةٖۖ وَزَوَّجۡنَٰهُم بِحُورٍ عِينٖ ٢٠

17. Lalle masu tsoron Allah suna cikin gidajen Aljanna da ni’ima.

18. Suna masu more abin da Ubangijisu Ya ba su, Ubangijinsu kuma Ya tserar da su daga azabar Jahima.

19. Ku ci ku sha cikin jin ɗaɗi saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa.

20. Kuna masu kishingiɗa a kan gadaje waɗanda aka jera su sahu-sahu; Muka kuma aura musu ‘yan matan Hurul-Ini.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon masu taƙawa, watau masu kiyaye dokokinsa; suna bin umarninsa suna kuma guje wa haninsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, a lahira za a kai su gidan Aljanna cikin wata ni’ima mai girma marar yankewa har abada, suna gidajensu na Aljanna suna morewa da kayayyakin jin daɗi da Allah Ubangijinsu ya tanadar musu na ci da na sha da auratayya, ya kuma tserar da su daga azabar wutar Jahimu. Watau dai ya ba su duk abin da suke so, ya kuma kare su daga abin da suke ƙi, saboda sun aikata abin da yake so, sun guji abin da yake ƙi.
Bayan wannan ma, za kuma su riƙa jin maganganu masu daɗi na girmamawa, a riƙa ce musu, su ci su sha duk abin da ransu yake sha’awa cikin marmari da raha, hankalinsu kwance ba tare da suna fargabar wani abu zai cutar da su ba. Ana kuma tabbatar musu da cewa, wannan duka sakamakon kyawawan ayyukansu ne da suka kasance suna aikatawa a duniya.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani yanayi na jin daɗi da suke ciki, watau suna kishingiɗe a kan gadaje masu kwalliya waɗanda aka jera sahu-sahu, wasu na fuskantar wasu a jere da juna, kuma ƙari a kan haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aura musu matan Hurul-Ini, watau mata masu fararen idanuwa manya-manya, suna tare da su koyaushe suna ɗebe musu kewa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kyakkyawan salon wa’azi na Alƙur’ani yakan ambaci kyakkyawan sakamakon muminai bayan ya ambaci mummunan sakamakon masu laifi, watau yana haɗa tsakanin tsoratarwa da kwaɗaitarwa.

2. Bayanin girman falalar Allah ga muminai a ranar alƙiyama yayin da zai haɗa iyaye muminai da ‘ya’yansu muminai a wuri guda ko da aikinsu bai kai na iyayen ba a gidan Aljanna, domin ni’imarsa gare su ta kammala.

3. Tabbatar da cikar adalcin Allah, domin ba zai riskar da ‘ya’ya masu laifi da iyayensu masu laifi a wuri ɗaya a wutar Jahannama ba, saboda yin haka zai sanya a yi wa wani azabar da bai cancanci irinta ba.

4. Giyar Aljanna ba ta sanya maye ko sumbatu ko maganganun banza ga duk wanda ya sha ta.

5. Duk wanda ya ji tsoron Allah a duniya, to zai amintar da shi a lahira.

6. Mumini da kafiri kowannensu ba zai manta da halin da ya kasance a cikinsa a duniya ba. Mumini farin cikinsa zai ƙaru yayin da ya gan shi ya rabu da kurkukun duniya zuwa ni'imar Aljanna. Kafiri kuwa baƙin cikinsa zai ƙaru yayin da ya gan shi ya rabu da rayuwar ta-more ta duniya zuwa azabar Jahannama.

Suratuɗ Ɗur (21-28)

وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱتَّبَعَتۡهُمۡ ذُرِّيَّتُهُم بِإِيمَٰنٍ أَلۡحَقۡنَا بِهِمۡ ذُرِّيَّتَهُمۡ وَمَآ أَلَتۡنَٰهُم مِّنۡ عَمَلِهِم مِّن شَيۡءٖۚ كُلُّ ٱمۡرِيِٕۭ بِمَا كَسَبَ رَهِينٞ ٢١ وَأَمۡدَدۡنَٰهُم بِفَٰكِهَةٖ وَلَحۡمٖ مِّمَّا يَشۡتَهُونَ ٢٢ يَتَنَٰزَعُونَ فِيهَا كَأۡسٗا لَّا لَغۡوٞ فِيهَا وَلَا تَأۡثِيمٞ ٢٣ ۞وَيَطُوفُ عَلَيۡهِمۡ غِلۡمَانٞ لَّهُمۡ كَأَنَّهُمۡ لُؤۡلُؤٞ مَّكۡنُونٞ ٢٤ وَأَقۡبَلَ بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖ يَتَسَآءَلُونَ ٢٥ قَالُوٓاْ إِنَّا كُنَّا قَبۡلُ فِيٓ أَهۡلِنَا مُشۡفِقِينَ ٢٦ فَمَنَّ ٱللَّهُ عَلَيۡنَا وَوَقَىٰنَا عَذَابَ ٱلسَّمُومِ ٢٧ إِنَّا كُنَّا مِن قَبۡلُ نَدۡعُوهُۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡبَرُّ ٱلرَّحِيمُ ٢٨

21. Waɗanda kuwa suka yi imani, zuriyarsu kuma suka bi su a imani, za Mu haɗa su da zuriyarsu, ba kuma za Mu tauye musu komai ba na aikinsu. Kowane mutum jingina ne ga abin da ya tsuwurwurta.

22. Muka kuma daɗe su da abin marmari da nama irin wanda suke sha'awa.

23. A cikinta (Aljannar) suna musayan kofuna na giya da babu wani zancen banza game da ita, kuma babu wani zunubi.

24. Wasu yara nasu kuma waɗanda suke kamar lu'u-lu'un da yake cikin kwasfa suna kaiwa da komowa a kansu.

25. Kuma shashinsu ya fuskanci shashi suna tambayar juna.

26. Suka ce: "Lalle sanda muke cikin iyalinmu (a duniya) kafin wannan, mun kasance masu tsoron azabar Allah.

27. "Sai Allah Ya yi mana baiwa ya kiyaye mu azabar wuta.

28. "Lalle mu mun kasance a da can muna bauta masa; lalle shi Mai kyautatawa ne, Mai jin ƙai."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin cikakkiyar ni'imar da ya tanadar wa 'yan Aljanna, da cewa, duk waɗanda suka yi imani a nan duniya suka yi ayyuka nagari, sannan 'ya'yansu ma suka bi su a imani, to sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa su wuri guda a Aljanna, watau ya ɗaukaka darajar 'ya'yansu don su haɗu wuri ɗaya, ko da kuwa ayyukan 'ya'yan ba su kai na iyayen ba. Ya yi musu haka ne don ya cika musu farin cikinsu, ba kuma tare da ya tauye musu wani abu na ladansu ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah yana ɗaga zuriyar mumini zuwa gare shi har ya kai su zuwa ga matsayinsa, ko da kuwa ba su kai shi ba wajen aiki, don hakan ya faranta masa rai." Sai ya karanta wannan ayar. [Al-Bazzar #2260. Dubi, Al-Al-Bani, *As-Silsilatus Sahih*ah #2490].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikar adalcinsa ga bayinsa, inda ya tabbatar musu da cewa, kowane mutum ana tsare shi ga abin da ya aikata kaɗai, ba za a kama wani rai da laifin wani ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana ni'imomin 'yan Aljanna, yayin da za a daɗa kawo musu kayan marmari iri-iri waɗanda ransu yake so, da kuma nama irin wanda suke sha'awa. Bugu da

ƙari kuma za su riƙa musayan kofuna na giya a tsakaninsu, irin giyar da ba ta sanya mai shan ta wani zancen banza ko aikata wani laifi, kamar yadda yake faruwa ga wanda ya sha giyar duniya ya bugu.
Sannan kuma ga wasu yara matasa masu yi musu hidima suna kaiwa da komowa a kansu, ga su da haske kamar lu'u-lu'u da yake cikin kwasfansa wani abu bai ɓata shi ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Kowane ɗan'adam yana da hadimi dubu, kowane hadimi yana da aikinsa ba irin na ɗan'uwansa ba." [Ibn Jarir, *At-Tafsir* Juzu'i na 21, shafi na 641].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda 'yan Aljanna za su zauna suna tuna rayuwarsu ta duniya, yayin da wasu za su fuskanci juna suna tambayar junansu labaransu da yanayin rayuwarsu a duniya, sai su amsa wa juna da cewa a duniya suna cike da tsoron azabar Allah, wanda hakan ya sanya suka guji saɓa masa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu baiwar shiriya zuwa ga Musulunci, ya tsare su daga matsananciyar azaba. Suka kuma tabbatar wa da juna cewa sun kasance a duniya suna bautar Allah, suna kuma roƙon sa ya tsare su daga azabar wuta, domin shi mai kyautata wa bayinsa ne mai jin ƙan su ne, don haka ne ya shiryar da su ga imani, ya shigar da su gidan Aljanna, ya tsare su daga shiga wutar Jahannama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafiri bai tabbata cikin kafircinsa ba har sai da ya yi watsi da hankalin da Allah ya ba shi, domin da ya yi aiki da hankalinsa da ya riski hujjar gaskiyar da Manzon Allah (ﷺ) ya zo masa da ita, ya kuma gane munin hanyar da yake kai ta kafirci da ɓata.

2. Mushirikai sun nuna rashin hankalinsu da wautarsu a fili, domin sun kira Manzon Allah da mawaƙi da boka, sannan kuma suka ce mahaukaci ne, sun manta da cewa babu yadda za a yi mahaukaci ya zamanto mai fasaha da hikimar waƙa ko ya zama boka tare da cewa shi boka mutum ne mai dabara da wayo da kaifin ƙwaƙwalwa, mahaukaci kuma ba shi da hankali ballantana ya zama mai kaifin basira.

3. Ba zai yiwu bisa ga al'ada ba a samu mutane waɗanda suke madaidaita da junansu, amma ɗaya daga cikinsu ya zo da abin da su duka ba za su iya kawo kamarsa ba. Duk wani mai hankali ba ya tabbatar da wani abu har sai ya zama mai ilimi a kansa. To har idan sun san cewa Manzon Allah ne ya ƙirƙiro Alƙur'ani, to wannan ya nuna su ma za su iya kawo kamarsa, domin Manzon Allah (ﷺ) kamarsu yake wajen fasaha, ya kuma haɗa gari ɗaya da dangantaka ta jini da su. Wasunsu ma sun zarce shi da iya rubutu da shirya waƙe da zama da masu ilimi da yin huɗubobi a cikin jama'a da rubuta wasiƙu zuwa ga sarakuna da sauransu, don haka ba zai iya zuwa da abin da zai gagare su ba sai idan yana samun wahayi ne da ƙarfafawa daga Allah.

Suratuɗ Ɗur (29-34)
فَذَكِّرۡ فَمَآ أَنتَ بِنِعۡمَتِ رَبِّكَ بِكَاهِنٖ وَلَا مَجۡنُونٍ ۝٢٩ أَمۡ يَقُولُونَ شَاعِرٞ نَّتَرَبَّصُ بِهِۦ رَيۡبَ ٱلۡمَنُونِ ۝٣٠ قُلۡ تَرَبَّصُواْ فَإِنِّي مَعَكُم مِّنَ ٱلۡمُتَرَبِّصِينَ ۝٣١ أَمۡ تَأۡمُرُهُمۡ أَحۡلَٰمُهُم بِهَٰذَآ أَمۡ هُمۡ قَوۡمٞ طَاغُونَ ۝٣٢ أَمۡ يَقُولُونَ تَقَوَّلَهُۥۚ بَل لَّا يُؤۡمِنُونَ ۝٣٣ فَلۡيَأۡتُواْ بِحَدِيثٖ مِّثۡلِهِۦٓ إِن كَانُواْ صَٰدِقِينَ ۝٣٤

29. To ka yi wa'azi, don ba za ka zama boka ba ko mahaukaci saboda ni'imar Ubangijinka.

30. A'a, cewa dai suka yi: "Shi mawaƙi ne da muke saurara masa hanyar halaka."

31. Ka ce, "To ku saurara, ni ma lalle ina cikin masu sauraron."

32. Ko kuwa hankullansu ne suke umartar su da wannan? A'a, su dai mutane ne masu tsaurin kai.

33. Ko kuwa suna cewa: "Ya ƙago shi?" A'a, su dai ba sa yin imani ne kawai.

34. To su zo da wani zance irinsa idan sun kasance masu gaskiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya ci gaba da yi wa mutane wa'azi da faɗakarwa, kada ya damu da masu ƙaryata shi, suna cutar da shi tare da mabiyansa, har suna jifan sa da miyagun maganganu da tuhumce-tuhumce na ƙarya, alhali kuwa sun san shi ciki da bai ba haka yake ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wanke shi daga duk wani aibi da suke liƙa masa, don haka shi ba boka ba ne ba kuma mahaukaci ba ne, domin Allah ya yi masa ni'imomi da dama, daga cikinsu har da kamalar hankali da guje wa shaiɗanu.
To amma duk da wannan sai wani lokaci su ce masa shi mawaƙi ne ba manzo ne daga Allah ba, don haka suna saurara masa ne har mutuwa ta zo ta ɗauke shi kowa ya huta. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya mayar musu da martani da cewa su ci gaba da sauraron mutuwarsa, shi ma yana nan yana sauraron azabar da za ta zo ta auka musu saboda kafircinsu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su cewa, shin munanan maganganun da suke jifan Manzonsa da su, hankulansu ne suka faɗa musu haka, watau su kira shi boka da mahaukaci a lokaci guda, su haɗa masa abubuwan da ba za su haɗu wuri guda ba? Watau idan har haka hankulansu suke, to tir da irin waɗannan hankula nasu. Ko kuma dai ɗagawarsu ce ta jefa su cikin wannan harigido suna ƙazafi suna ƙetare duk wata iyaka, ba sa aiki da lura balle shari'a. Tabbas wannan shi ne dalilin taɓewarsu da yawan maganganunsu na ƙarya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wai suna zargin Annabi (ﷺ) da cewa shi ne ya ƙagi Alƙur'ani ba wahayinsa aka yi masa ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da jawabi cewa ba haka ba ne, Manzon Allah (ﷺ) bai ƙagi Alƙur'ani ba, kawai dai saboda sun ƙi yin imani ne don girman kansu da bijirewarsu. Don haka sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalance su da cewa, tun da su ma Larabawa ne masu fasaha to su ƙago wani zance kamar na Alƙur'ani idan har su masu gaskiya ne game da abin da suke faɗa a kan Manzon Allah (ﷺ).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cewa, Allah ne kaɗai abin bauta, domin shi ne kaɗai mahalicci, wanda kuwa ya yi halitta shi ne ya cancanci a bauta masa.

2. Yarda da cewa Allah ne ya halicci kowa da komai a karon farko, yana nuna cewa shi mai iko ne ya sake dawo da wanda ya mutu a karo na biyu, domin farkon yin abu ya fi al'ajabi a kan maimaita shi.

3. Mushirikan Larabawa ba sa musu a kan cewa Allah ne mahaliccinsu sun yi jayayya ne kawai a kan taƙaita bauta a gare shi.

4. Taskokin arzuki duk na Allah ne, shi ne yake raba su yadda ya ga dama, ya ba wanda ya ga dama, ya hana wanda ya ga dama. Don haka shi ne mai ba da annabta ga wanda ya so ya zaɓa.

Suratuɗ Ɗur (35-38)

أَمْ خُلِقُواْ مِنْ غَيْرِ شَيْءٍ أَمْ هُمُ ٱلْخَٰلِقُونَ ﴿٣٥﴾ أَمْ خَلَقُواْ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَۚ بَل لَّا يُوقِنُونَ ﴿٣٦﴾ أَمْ عِندَهُمْ خَزَآئِنُ رَبِّكَ أَمْ هُمُ ٱلْمُصَيْطِرُونَ ﴿٣٧﴾
أَمْ لَهُمْ سُلَّمٌ يَسْتَمِعُونَ فِيهِۖ فَلْيَأْتِ مُسْتَمِعُهُم بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿٣٨﴾

35. Ko kuwa an halicce su ne ba da wani mai halitta ba, ko kuwa su ne masu halittar (kansu)?

36. Ko kuwa su suka halicci sammai da ƙasa? A'a, ba sa dai sakankancewa ne.

37. Ko kuwa taskokin Ubangijinka suna wurinsu ne, ko kuwa su ne masu iko?

38. Ko kuwa suna da wani tsani ne da suke jiyo (zancen Allah) ta kansa? To mai jiyowar tasu ya zo da wata hujja mabayyaniya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai masu musunta Kaɗaitakarsa wajen bauta da ƙaryata Manzonsa (ﷺ) da tashi bayan mutuwa wanda yake nuna rashin imaninsu da cikar Kudura da iko na Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jefa musu wasu tambayoyi da ba su da wata amsa da za su iya bayarwa sai dai yarda da sallama wa Kudurar Allah a kan komai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su cewa, shin haka kawai suka faɗo duniya ba tare da wani mahalicci ba, watau samuwa kawai suka yi ba tare da wani ya samar da su ba? Su kansu sun san wannan abu ba zai taɓa yiwuwa a hankali ba. Ko kuma su ne suka halicci kawunansu? Wannan ma sun san ba zai taɓa faruwa ba, domin kuwa sun san ba za a taɓa samun wani mahaluƙi ba tare da mahalicci ba, hakanan ba zai yiwu wani mahaluƙi ya yi halitta ba, to me ya hana su bauta wa mahaliccinsu Allah shi kaɗai?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tambayar su cewa, shin su ne suka halicci sammai da ƙasa, don haka suka zamanto suna tarayya da Allah wajen yin halittar? Wannan ma sun san ba haka ne ba, to me ya hana su bautar Allah shi kaɗai? Me kuma ya sanya suke ƙaryata tashi bayan mutuwa? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, musabbabin haka shi ne rashin yaƙini da sakankancewa da hujjojin da Allah ya bayyana musu shi ne ya kai su ga ƙaryata gaskiya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tambayar su game da taskokin arzukinsa da rahamarsa cewa, shin a hannunsu suke, suna zaɓar wanda suka ga dama su ba shi, su hana wanda suka ga damar hanawa, don haka suka ga damar hana wa Annabi (ﷺ) annabci, ko kuwa dai su ne masu iko da komai na halittar Allah, suna yin abin da suke so? Lalle sun tabbata ba haka abin yake ba, to me ya sanya su ƙaryata manzancin Annabi (ﷺ) har su riƙa jifan sa da tuhumce-tuhumce na banza?
Sannan ya sake tambayar su game da dagewar da suke a kan cewa su ne masu gaskiya Annabi (ﷺ) maƙaryaci ne da cewa, shin suna da wani tsani ne da suke hawa sama da shi inda suka jiyo wahayi daga Allah na cewa lalle su ne masu gaskiya? To idan sun ce haka ne, to mai jiyo musu wahayin ya zo da wata hujja bayyananna da za ta gaskata su a kan da'awarsu. Sun tabbata haka ma ba mai yiwuwa ba ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsarkake Allah daga duk wata naƙasa ko tawaya, don haka bai kyautu a danganta masa haihuwar 'ya'ya maza ko mata ba.

2. Saboda tsananin rashin girmama Allah ya sa mushirikai suke danganta masa 'ya'ya mata a lokacin da su kuma suke ƙyamar su.

3. Bai halatta mai wa'azi ya sharɗanta a biya shi wani lada ba kafin ya isar da saƙon Allah.

4. Babu wani abu na ilimi da mushirikan Larabawa suka dogara da shi wajen ƙaryata Manzon Allah (ﷺ), domin ya same su al'umma ce wadda ba ta rubutu ba ta karatu, suna rayuwa cikin duhun jahilci, sai ya zo musu da hasken Musulunci.

5. Duk masu nufin Musulunci da Musulmi da wani makirci, to daga ƙarshe kansu makircinsu zai koma. Don haka masu gaskiya su nutsu su dogara ga Allah, kada wani maƙiyinsu ya ba su tsoro har su daina abin da suke yi na yaɗa addininsu.

Suratuɗ Ɗur (39-43)
أَمْ لَهُ ٱلْبَنَٰتُ وَلَكُمُ ٱلْبَنُونَ ﴿٣٩﴾ أَمْ تَسْـَٔلُهُمْ أَجْرًا فَهُم مِّن مَّغْرَمٍ مُّثْقَلُونَ ﴿٤٠﴾ أَمْ عِندَهُمُ ٱلْغَيْبُ فَهُمْ يَكْتُبُونَ ﴿٤١﴾ أَمْ يُرِيدُونَ كَيْدًا ۖ فَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ هُمُ ٱلْمَكِيدُونَ ﴿٤٢﴾ أَمْ لَهُمْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ ۚ سُبْحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٤٣﴾

39. Ko kuwa Shi ne zai zama mai 'ya'ya mata, ku kuwa ku zamanto da 'ya'ya maza?

40. Ko kuwa kana tambayar su wani lada ne, saboda haka bashi ya yi musu nauyi?

41. Ko kuwa sun san gaibu ne, saboda haka su ne suke rubutawa.

42. Ko kuwa suna nufin (yi maka) makirci ne? To waɗanda suka kafirce su ne waɗanda makircinsu zai kama su.

43. Ko kuwa suna da wani abin bauta ne ba Allah ba? Tsarki ya tabbata ga Allah daga abin da suke tara (Shi da shi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar wa da mushirikan Larabawa martani a kan da'awarsu ta cewa mala'iku 'ya'yan Allah ne mata, inda ya nuna musu rashin adalcinsu har a cikin ƙaryar da suke yi, domin ta yaya za su danganta wa Allah 'ya'ya mata alhalin su suna ƙin su, su kuma su zaɓa wa kansu 'ya'ya maza? Don haka a nan sun haɗa munanan abubuwa biyu a tare, da farko sun jingina wa Allah ɗa, alhalin bai haifa ba, ba a haife shi ba. Na biyu kuma suka zaɓa masa 'ya'ya mata waɗanda su ba sa son su, har ma suka ce su ne 'ya'yan Allah. Yanzu akwai tauye haƙƙin da ya kai wannan?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi Manzonsa (ﷺ) game da bijirewar da mushirikai suke yi masa cewa, ko yana neman su riƙa ba shi wani lada ne game da saƙon da yake isar musu, su kuma suka kasa biyan sa, don haka suka ƙi ba da gaskiya da shi?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tambayar su cewa, ko suna da ilimin gaibu ne, don haka suna gano abubuwan da mutane ba su sani ba, sai suka riƙa rubuta su? Watau ta haka ne suka samo ilimin da ya fi wanda Annabi (ﷺ) ya zo musu da shi ko ya saɓa masa, saboda haka suka ƙi yin imani da shi. Lalle su ma sun tabbata ba haka abin yake ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, to idan duk abin ba haka yake ba, to su mushirikai masu sukan Manzon Allah suna ƙaryata shi, suna nufin yi masa makirci ne da niyyar su kuma cutar da shi su cutar da addininsa? To sai Allah ya umarci Manzon Allah (ﷺ) ya sami nutsuwa ya dogara ga Allah, waɗannan kafirai su ne makircin zai ci, ba zai shafe shi da komai ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tambayar su cewa, shin suna da wani abin bauta ne da gaskiya ba Allah ba, wanda yake amfanar da su ko ya cutar da su? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkake kansa daga duk wani abokin tarayya da suke danganta masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin taurin kan kafirai da bijire wa hujjoji komai ƙarfinsu da bayyanarsu.

2. Babu wata hanya da kafirai za su ƙwaci kansu a ranar alƙiyama, hakanan ba su da masu ƙwatar su.

3. Tabbatar da azabar ƙabari.

4. Haƙuri da kuma bauta wa Allah suna taimaka wa bawa wajen fuskantar duk wata matsala ta rayuwa da makirce-makircen maƙiya.

Suratuɗ Ɗur (44-49)

وَإِن يَرَوْاْ كِسْفًا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ سَاقِطًا يَقُولُواْ سَحَابٌ مَّرْكُومٌ ﴿٤٤﴾ فَذَرْهُمْ حَتَّىٰ يُلَٰقُواْ يَوْمَهُمُ ٱلَّذِى فِيهِ يُصْعَقُونَ ﴿٤٥﴾ يَوْمَ لَا يُغْنِى عَنْهُمْ كَيْدُهُمْ شَيْـًٔا وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿٤٦﴾ وَإِنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ عَذَابًا دُونَ ذَٰلِكَ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٤٧﴾ وَٱصْبِرْ لِحُكْمِ رَبِّكَ فَإِنَّكَ بِأَعْيُنِنَا ۖ وَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ حِينَ تَقُومُ ﴿٤٨﴾ وَمِنَ ٱلَّيْلِ فَسَبِّحْهُ وَإِدْبَٰرَ ٱلنُّجُومِ ﴿٤٩﴾

44. Da kuwa za su ga wani yanki na azaba mai faɗowa daga sama da sai su ce: “Hadari ne haɗaɗɗe.”

45. To ka rabu da su har sai sun haɗu da ranarsu wadda za a karɓi rayukansu a cikinta.

46. Ranar da makircinsu ba zai maganta musu komai ba, kuma su ba za a taimake su ba.

47. Lalle kuma waɗanda suka yi zalunci suna da wata azabar daban ban da wannan (ta lahira), sai dai kuma mafi yawansu ba su sani ba.

48. Kuma ka yi haƙuri da hukuncin Ubangijika, don ko lalle kana ƙarƙashin lurarmu; kuma ka yi tasbihi da yabon Ubangijinka lokacin da za ka tashi (daga bacci).

49. Da daddare kuma sai ka tsarkake Shi da kuma lokacin da taurari suka ba da baya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin taurin kan mushirikai da ƙaryata gaskiya bayan duk wasu dalilai sun tabbata, don haka ba abin da zai dace da su sai azabar Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, taurin kansu ya kai ta yadda ko da ma za su ga wani yanki na azaba ya taho gadan-gadan zai faɗo musu daga sama, to ba za su yarda da cewa azabar Allah ce ta zo musu ba, sai dai su riƙa cewa ai haɗari ne ya haɗo wani kan wani zai saukar musu da ruwa, don haka ba za su wa’azantu ba ballantana su yi imani.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya fita batunsu, ya ci gaba da wa’azinsa, domin sun kasance mutane ne da babu abin da zai yi maganin taurin kansu sai sun haɗu da ranar da za su gamu da azaba sun gan ta a fili babu sauran wani musu, watau ranar alƙiyama. A ranar duk wani makircinsu ba zai amfana musu komai ba, kuma ba su da waɗanda za su taimaka musu su kuɓutar da su daga azabar Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, waɗanda suka zalunci kawunansu da shirka da saɓon Allah suna da wata azaba ta daban tun kafin su haɗu da azabar lahira, watau a nan duniya za su iya gamuwa da azabar kisa a wurin yaƙi ko kamawa a matsayin ribatattun yaƙi, sannan idan sun mutu su haɗu da azabar ƙabari, to amma duk da irin wannan gargaɗi da ake yi musu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, yawancinsu ba su san haka ba, don haka ba za su taɓa rabuwa da kafircinsu ba.

Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana rugujewar duk abin da mushirikai suke kai na shirka da ƙaryata Manzon Allah da yi masa izgili, sai a ƙarshen wannan Surar ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya ci gaba da haƙuri da hukuncin Allah bisa duk abin da zai same shi marar daɗi, ya tabbatar masa cewa yana ƙarƙashin kulawarsa da kiyayewarsa, shi dai kawai ya ci gaba da bautar Allah Ubangijinsa yana tsarkake shi da tasbihi tare da gode masa duk lokacin da ya tashi daga barci. Hakanan da daddare ya tsarkake shi da yin tasbihi yayin sallolin dare, ya kuma sallaci sallar Asuba lokacin da taurari suka ba da baya yayin da hasken alfijir ya bayyana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alaƙar rantsuwar Allah da tauraro a nan shi ne, akwai babbar alaƙa tsakanin taurari masu haskaka sararin samaniya da kuma wahayin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi yana karanta wa mutane. Kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya taurari suka zama ado a sararin samaniya, to hakanan shi ma wahayi yake ado ne ga ƙasa. Ba domin ilimin da annabawa suke bari gado ba, to da mutane sun rayu cikin duhu ƙirin wanda ya fi na dare mai tsananin duhu.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta Annabi (ﷺ) da cewa shi mutumin mutanen Makka ne, domin ya nuna musu cewa, ai sun san shi sarai, sun kuma san tasowarsa ciki da waje tun bai zama Annabi ba, sun san shi mutum ne mai gaskiya da riƙon amana da nutsuwa, to amma sai ga shi yanzu don ya zo yana faɗa musu gaskiya sun kira shi da marar hankali. Wannan babu shakka son zuciya ne ƙarara.

3. Tabbatar da dalili a kan cewa sunnar Annabi (ﷺ) ita ma wahayi ce daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma shi Annabi (ﷺ) ma'asumi ne game da duk wani abu da yake isarwa na shari'a, domin ba ya maganar son zuciya sai abin da ake yi masa wahayi da shi.

4. Falalar Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya keɓance shi don ya zama malami ga Annabi (ﷺ) yana karanta masa Alƙur'ani, don haka shi malamin Annabi Muhammadu ne.

5. Ba da kariya ga wahayi, watau Alƙur'ani da tsare shi daga shaiɗanu ta yadda ba za su iya jirkita shi ba ko su su jefa ƙarnarsu a cikinsa, domin wanda yake zuwa da shi mai tsananin ƙarfi ne, watau babu wani shaiɗani da zai iya kusantar sa ballantana ya lalata masa aikensa.

6. Mala'iku halittu ne masu kyan sura masu tsananin ƙarfi.

7. Annabi (ﷺ) ya ga Jibrilu a surarsa wadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicce shi da ita a daren Mi'iraji.

8. Cikar ladabin Annabi (ﷺ). Ba a taɓa yin mutum mai ladabi a wurin Allah ba tun kafuwar duniya har zuwa tashin alƙiyama kamar Manzon Allah (ﷺ) ba.

9. Tabbatar da cewa, Annabi (ﷺ) ya ga Aljanna da wuta a daren mi'iraji.

53-Suratun Najm

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da suna *'Suratun Najm'*, kamar yadda ya zo a cikin hadisin Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya kara masa yarda), ya ce: Annabi (ﷺ) ya karanta '*Suratun Najm*i' sai ya yi sujjada (watau a ƙarshenta), sai kowa daga cikin mutanensa (Musulmi da mushirikai) suka yi sujjada in ban da mutum ɗaya, shi sai ya cika tafin hannunsa da ƙasa ya kai goshinsa ya ce: "Wannan ya ishe ni." Abdullahi ya ce: "Na ga wannan mutumin daga baya an kashe shi yana kafiri." [Bukhari #1070]. Wannan mutumin shi ne Umayyatu ɗan Khalaf.
A wasu littattafan hadisai, kamar Bukhari da Tirmizi an kira ta da suna '*Suratu Wan-Najmi'*, watau kamar yadda lafazin ya zo a cikin Alƙur'ani.

2. Sanda Aka Saukar da Ita:
Sura ce Makkiyya gaba ɗayanta a wurin dukkan malamai.

3. Jerin Saukarta
Ita ce Sura ta ishirin da uku (23) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Ikhlas*' kafin '*Suratu Abasa*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Malaman Kufa suna ganin ayoyinta sittin da biyu ne (62) amma yawancin masu lissafin ayoyi na sauran garuruwa sun ce sittin da ɗaya ne (61).

5. Babban Jigonta
Tana Magana ne a kan tabbatar da gaskiyar wahayi da bayanin asalinsa mai daraja, domin tabbatar da Tauhidi da rushe shirka.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tabbatar da gaskiyar Manzon Allah (ﷺ) game da abin da yake isarwa daga Allah da tsarkake shi daga duk wata tuhuma da mushirikai suke yi masa.
• Tabbatar da cewa, Alƙur'ani wahayi ne daga Allah wanda Mala'ika Jibirilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo da shi ga Annabi (ﷺ).
• Bayanin siffofin Mala'ika Jibirilu da yadda yake sauka da wahayi.
• Rushe da'awar da mushirikai suke yi ta cewa gumakansu Lata da Uzza da Manata, duk 'ya'yan Allah ne mata, da tabbatar musu cewa, duk waɗannan gumaka tatsuniyoyi ne ba su da wani tushe ballantana asali.
• Bayanin sakamakon bijirarru da shiryayyu da gargaɗin su a kan su guji maganganu game da gaibu ta hanyar zato kawai ba tare da wata hujja ba.
• Tabbatar da tashi bayan mutuwa.

• Tunatar da su azabar Allah ga al’ummun da suka shuɗe gabaninsu da kuma manzannin da suka zo da shari’u kafin Manzon Allah (ﷺ).
• Tsoratar da su wata azaba wadda take dab da ta auka musu.

Suratun Najm (1-18)
وَٱلنَّجۡمِ إِذَا هَوَىٰ ۝١ مَا ضَلَّ صَاحِبُكُمۡ وَمَا غَوَىٰ ۝٢ وَمَا يَنطِقُ عَنِ ٱلۡهَوَىٰٓ ۝٣ إِنۡ هُوَ إِلَّا وَحۡيٞ يُوحَىٰ ۝٤ عَلَّمَهُۥ شَدِيدُ ٱلۡقُوَىٰ ۝٥ ذُو مِرَّةٖ
فَٱسۡتَوَىٰ ۝٦ وَهُوَ بِٱلۡأُفُقِ ٱلۡأَعۡلَىٰ ۝٧ ثُمَّ دَنَا فَتَدَلَّىٰ ۝٨ فَكَانَ قَابَ قَوۡسَيۡنِ أَوۡ أَدۡنَىٰ ۝٩ فَأَوۡحَىٰٓ إِلَىٰ عَبۡدِهِۦ مَآ أَوۡحَىٰ ۝١٠ مَا كَذَبَ ٱلۡفُؤَادُ مَا رَأَىٰٓ ۝١١
أَفَتُمَٰرُونَهُۥ عَلَىٰ مَا يَرَىٰ ۝١٢ وَلَقَدۡ رَءَاهُ نَزۡلَةً أُخۡرَىٰ ۝١٣ عِندَ سِدۡرَةِ ٱلۡمُنتَهَىٰ ۝١٤ عِندَهَا جَنَّةُ ٱلۡمَأۡوَىٰٓ ۝١٥ إِذۡ يَغۡشَى ٱلسِّدۡرَةَ مَا يَغۡشَىٰ ۝١٦ مَا زَاغَ
ٱلۡبَصَرُ وَمَا طَغَىٰ ۝١٧ لَقَدۡ رَأَىٰ مِنۡ ءَايَٰتِ رَبِّهِ ٱلۡكُبۡرَىٰٓ ۝١٨

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da tauraro yayin da ya faɗi.

2. Mutumin naku bai ɓata ba, kuma bai kauce hanya ba.

3. Kuma ba ya yin magana bisa son rai.

4. Shi (Alƙur'ani) ba wani abu ne ba in ban da wahayi da ake yiwo (masa).

5. Mai tsananin ƙarfi ne (watau Jibrilu) ya koyar da shi.

6. Mai kyawawan halitta ne, sai ya daidaita.

7. Alhali kuwa shi yana a sassa na can sama.

8. Sannan sai ya kusanto, sai ya ƙara matsawa.

9. Sai ya kasance kamar kusancin kamu biyu ko ƙasa da haka.

10. Sannan (Allah) Ya yiyo wahayin abin da Ya yi wahayi zuwa ga Bawansa (Ma’aiki).

11. Zuciyar (ta Ma’aiki) ba ta yi ƙaryar abin da ta gani ba.

12. Yanzu kwa riƙa jayayya da shi kan abin da yake gani?

13. Haƙiƙa ya gan shi (Jibrilu) a wani karon ma.

14. A wurin Magaryar tuƙewa.

15. A wurinta ne Aljannar makoma take.

16. A yayin da abin da ya lulluɓe Magaryar (na ban mamaki) ya lulluɓe ta.

17. Ganin (nasa) bai karkace ba, kuma bai zarme ba.

18. Haƙiƙa ya ga wasu ayoyin Ubangijinsa manya-manya.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da tauraro yayin da ya faɗi a ƙarshen dare, domin ya tabbatar wa mushirikai cewa mutuminsu, watau Annabi Muhammadu (ﷺ) bai ɓata ya kauce wa hanyar gaskiya ba, bai kuma zama mai sani ya take saninsa ba. Shi mutum ne da yake kan hanyar gaskiya kuma yana aiki da ita. Kuma ba ya magana ta son zuciya. Duk abin da yake karanta musu na Alƙur'ani da wanda yake sanar da su na shari'a ba wani abu ne ba illa wahayi daga Allah, Mala'ika mai tsananin ƙarfi ne ya koyar da shi, watau Jibirilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta Jibirilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa shi mai kyakkyawar halitta ne, kuma ya daidaita a zahiri a cikin surarsa da Allah ya halicce shi da ita ta mala'ika a lokacin yana can a cikin sassa na sama sosai. Sannan sai ya kusanto Annabi (ﷺ) ya sake matsowa kusa da shi, har sai da kusancinsa da shi ya zamanto kamar kusancin kamu biyu ko ma ƙasa da haka. Sai Jibirilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wahayi zuwa ga bawan Allah Annabi Muhammadu (ﷺ) na abin da ya yi masa wahayi da shi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, zuciyar Manzon Allah (ﷺ) ba ta yi ƙaryar abin da idanunsa suka gani ba, watau jinsa da ganinsa da zuciyarsa duk sun haɗu a kan tabbatar da abu ɗaya na wahayi da Jibirilu ya yi masa ba su sassaɓa wa juna ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi mushirikai cewa, to yanzu su suna jayayya da Annabi ne (ﷺ) game da abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna masa a daren Isra'i na manya-manyan ayoyinsa?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ga Mala'ika Jibirilu a surarsa ta mala'ika da Allah ya halicce shi da ita a wani ƙaro na daban, watau a daren Isra'i a wurin Magaryar tuƙewa, wata bishiya ce babba da ke saman sama ta bakwai, inda duk wani abu da ya hau sama yake tuƙewa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a wurin wannan bishiyar Aljannar makoma take. Kuma wani babban al'amari na Allah ne yake lulluɓe ta wanda babu mai iya siffanta shi sai Allah.
Sai kuma ya bayyana cikar ladabin Manzon Allah (ﷺ) da nutsuwarsa lokacin da Allah ya tsayar da shi wannan matsayi, ganinsa bai karkata dama ko hagu ba, bai kuma ƙetare iyakar da ya shata masa ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda), yana cewa: "Manzon Allah (ﷺ) ya ga Ubangijinsa da zuciyarsa sau biyu." [Muslim #171 da Ahmad #1958].

An karɓo daga Masruƙ ya ce: A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce masa: "Ya kai baban A'isha, duk wanda ya riya cewa Muhammadu ya ga Ubangijinsa, to ya yi wa Allah babbar ƙarya." Ya ce: Na kasance ina kishingiɗe sai na miƙe zaune na ce: "Ya Uwar Muminai, ki saurara mini kada ki yi mini gaggawa, me za ki ce game da faɗar Allah: "Haƙiƙa ya gan shi a wani karon ma", da kuma faɗarsa: "Haƙiƙa ya gan shi a sararin (samaniya) mabayyani"? Sai ta ce: "Wannan Jibrilu ne; ya gan shi a wani lokaci a surarsa da aka halicce shi da ita; ya sake ganin sa a wani lokaci na biyu yayin da yake sauka daga sama zuwa ƙasa, girman halittarsa ta cika sama da ƙasa." Ta ce: "Ni ce farkon wanda na yi wa Manzon Allah (ﷺ) tambaya game da wannan ayar, sai ya ce: "Ai Jibrilu ne." [Bukhari #3235 da Muslim #177].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "An nuna mini Magaryar tuƙewa a sama ta bakwai, 'ya'yanta kamar kulolin Hajar, ganyenta kuwa kamar kunnuwan giwaye. Daga kututturan itacenta wasu ƙoramu suna fita, biyu a waje, biyu kuma a ciki, sai na ce: "Ya Jibrilu mene ne waɗannan?" Sai ya ce: Koramu biyu na ciki daga Aljanna ne, amma na waje su ne Nilu da Furata." [Ahmad #12673, Dubi Bukhari #3207 da Muslim #173].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lokacin da na isa wajen Magaryar tuƙewa, sai na ga ganyenta kamar kunnuwan giwaye, ‘ya’yanta kuwa kamar tuluna. Yayin da abin da ya lulluɓe ta daga al’amarin Allah ya lulluɓe ta sai ta rikiɗa ta zama yaƙutu da zumarradu da kwatankwacinsu.” [Ahmad #12301 da Ibn Jarir, Tafsiri, Juzu’i na 22 shafi na 36].

A wata ruwayar ya ce: “Yayin da abin da ya lulluɓe ta na al’amarin Allah ya lulluɓe ta sai ta rikiɗa, babu wanda zai iya siffanta ta saboda kyanta.” [Muslim #162].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, a daren Mi’iraji Annabi Muhammadu (ﷺ) ya ga manya-manyan ayoyin Ubangijinsa masu nuna cikar Kudurarsa, ya ga Aljanna ya kuma ga wuta da abubuwan ban mamaki da dama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu zaluncin da ya kai na wanda zai fifita wani mahaluƙi a kan Allah Mahalicci.

2. Duk wani addini da Allah bai saukar masa wata hujja ba to addinin ƙarya ne, kuma ɓata ne.

3. Mushirikai waɗanda suka bauta wa gumaka ba Allah ba, ba su dogara da wata hujja ba ko wani yaƙini, sun gina addininsu ne kawai a kan shaci-faɗi da zato marar tushe da son zuciya da jahilci. Waɗannan abubuwa su ne suka jefa su cikin ɓata da hallaka.

4. Musulunci ya zo ne da shiriya a komai; ya zo da shiriya a babin Tauhidi da annabta da dukkan ɓangarorin shari’a da mu’amala da siyasa da halayya da tattalin arzuki da sauran ɓangarorin rayuwa.

5. Ba duk abin da mutum yake buri yake samu ba. Komai na Allah ne, shi ne yake ba wa wanda ya so ya hana wanda ya ga dama.

6. Ba a samun ceto sai da sharaɗi biyu:
Na farko, izinin Allah ga shi mai yin ceton.
Na biyu, yardar Allah ga wanda za a ceta.

Suratun Najm (19-26)
أَفَرَءَيْتُمُ ٱللَّٰتَ وَٱلْعُزَّىٰ ﴿١٩﴾ وَمَنَوٰةَ ٱلثَّالِثَةَ ٱلْأُخْرَىٰٓ ﴿٢٠﴾ أَلَكُمُ ٱلذَّكَرُ وَلَهُ ٱلْأُنثَىٰ ﴿٢١﴾ تِلْكَ إِذًا قِسْمَةٌ ضِيزَىٰٓ ﴿٢٢﴾ إِنْ هِىَ إِلَّآ أَسْمَآءٌ سَمَّيْتُمُوهَآ أَنتُمْ
وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلْطَٰنٍ ۚ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَمَا تَهْوَى ٱلْأَنفُسُ ۖ وَلَقَدْ جَآءَهُم مِّن رَّبِّهِمُ ٱلْهُدَىٰٓ ﴿٢٣﴾ أَمْ لِلْإِنسَٰنِ مَا تَمَنَّىٰ ﴿٢٤﴾
فَلِلَّهِ ٱلْءَاخِرَةُ وَٱلْأُولَىٰ ﴿٢٥﴾ ۞ وَكَم مِّن مَّلَكٍ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ لَا تُغْنِى شَفَٰعَتُهُمْ شَيْـًٔا إِلَّا مِنۢ بَعْدِ أَن يَأْذَنَ ٱللَّهُ لِمَن يَشَآءُ وَيَرْضَىٰٓ ﴿٢٦﴾

19. Ku ba ni labarin (gumakan) Lata da Uzza.

20. Da Manata cikon ta ukunsu.

21. Yanzu ɗa namiji zai zama naku, Shi kuma Ya tashi da 'ya mace?

22. Idan haka ne wannan rabon na zalunci ne.

23. Su ba komai ba ne face sunaye da kuka sa musu, ku da iyayenku, Allah bai saukar muku da wata hujja ba game da su. Ba abin da suke bi sai zato da son zuciya. Hakika kuwa shiriya ta zo musu daga Ubangijinsu.

24. Ko kuwa sai mutum ya sami abin da yake buri ne?

25. To lahira da duniya duka na Allah ne.

26. Mala'iku nawa ne a cikin sammai cetonsu ba ya amfanar da komai sai da izinin Allah ga wadanda Ya ga dama Ya kuma yarda (da shi)?

A wadannan ayoyi Allah (Mai tsarki da daukaka) ya bayyana rushewar addinin mushirikai masu bautar gumaka ba Allah ba wadanda ba za su amfane su ko su cutar da su ba. Allah (Mai tsarki da daukaka) ya tambaye su game da gumakansu: Lata da Uzza da Manata ta cikon ukunsu, shin suna yi masu wani amfani ne ko suna iya cutar da su da wani abu? Sun tabbata ba sa iya yi musu komai daga cikin wadannan abubuwa biyu, to wane rashin hankali ne ya kai su ga bauta musu da ba su matsayin Allah (Mai tsarki da daukaka)?
Sannan Allah (Mai tsarki da daukaka) ya bayyana rashin ladabinsu gare shi, da tsabar zalunci da suke nunawa game da sha'aninsa, domin suna jingina masa 'ya'ya mata suna cewa su ne mala'iku. Su kuma suna zaba wa kawunansu 'ya'ya maza suna fifita su a kan mata. Allah ya tabbatar musu cewa, da abin haka yake, to da wannan rabo nasu ya zama rabon zalunci, domin yana kunshe da fifita mahaluki a kan Mahalicci Allah.
Kuma su gumakan da suke bauta ba Allah ba ba komai ba ne sai sunayen banza da suka kirkira su da iyayensu suka lakaba wa gumakan, amma ko kadan ba su cancanci a bauta musu ba, domin babu wata hujja da Allah ya saukar a kan haka. Mushirikai ba su gina addininsu a kan komai ba sai zunzurutun zato marar tushe da abin da soye-soyen zukatansu da shaidanunsu suke kawata musu suna bi suna aiki da shi, alhali sun yi watsi da shiriyar Allah, ga ta kuma tabbas Manzo ya zo musu da ita daga Ubangijinsu.
Allah (Mai tsarki da daukaka) ya bayyana cewa, duk da wannan bata da rashin hankalin da kafirai suke ciki da sunan addini, wai amma suna burin samun wani tagomashi a cikinsa. Allah (Mai tsarki da daukaka) ya tabbatar musu cewa, abin da suke buri na samun ceton gumakansu ba mai samuwa ba ne, domin kuwa ba duk abin da mutum yake buri yake samu ba, domin al'amura ba a hannunsa suke ba, komai yana karkashin mulkin Allah, don shi ne mai mulkin lahira da duniya duka, don haka yana ba wa wanda ya ga dama abin da ya ga dama a cikinsu, yana kuma hana wanda ya ga damar hanawa.
Sannan Allah (Mai tsarki da daukaka) ya soki bautar mala'iku da wasu suke yi suna tsammanin za su cece su a wurin Allah a ranar alkiyama. Allah (Mai tsarki da daukaka) ya tabbatar musu cewa, mala'iku da dama a cikin sammai cetonsu ba zai amfanar da komai ba sai bayan Allah (Mai tsarki da daukaka) ya ba su izinin yin ceto ga wanda ya ga damar su ceta ya kuma yarda da shi. Don haka mushirikai su san da cewa, Allah ba zai taba ba da izinin a ceci wanda yake yi masa shirka ba.

Daga wadannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rashin imanin mushirikai da ranar lahira, shi ne ya ba su karfin gwiwar fadar miyagun maganganu game da Allah da Manzonsa da mala'ikunsa.

2. Tsantsar zato kawai ba zai taba zama hujja mai tabbatar da gaskiya ba.

3. Duk wanda ya sanya duniya a gabansa ta zama ita ce kololuwar manufarsa, to ba zai taba wa'azantuwa da abin da ake fada masa ba; koyaushe zai zama mai bijire wa gaskiya don ta ci karo da manufarsa ta duniya.

4. Waɗanda ba su yi imani da ranar lahira ba, ba su da wani abu da suka ɗauka ilimi sai wanda ya danganci rayuwar duniya da moriyarta kawai. Amma ilimin sanin littafin Allah da sunnar Manzonsa, wanda da shi ne zukata sukan rayu su tsarkaka, mutum ya gane hanyar gaskiya ya bi ta, wannan a gunsu ba ilimi ne ba.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mafi sanin bawan da ya dace da shiriya sai ya shiryar da shi da falalarsa da wanda ya fi dacewa da ɓata sai ya ɓatar da shi da adalcinsa.

Suratun Najm (27-30)

إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ لَيُسَمُّونَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ تَسۡمِيَةَ ٱلۡأُنثَىٰ ٢٧ وَمَا لَهُم بِهِۦ مِنۡ عِلۡمٍۖ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّۖ وَإِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغۡنِي مِنَ ٱلۡحَقِّ شَيۡـٔٗا ٢٨ فَأَعۡرِضۡ عَن مَّن تَوَلَّىٰ عَن ذِكۡرِنَا وَلَمۡ يُرِدۡ إِلَّا ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ٢٩ ذَٰلِكَ مَبۡلَغُهُم مِّنَ ٱلۡعِلۡمِۚ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعۡلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِمَنِ ٱهۡتَدَىٰ ٣٠

27. Lalle waɗanda ba sa yin imani da ranar lahira suna kiran mala’iku da sunan mata.

28. Kuma ba su da wani ilimi game da haka; ba abin da suke bi sai zato; shi kuma zato, lalle ba ya wadatar da komai game da gaskiya.

29. Sai ka kau da kai daga duk wanda ya ba da baya daga ambatonmu, bai kuma yi nufin komai ba sai rayuwar duniya..

30. Wannan ne maƙurar iliminsu. Lalle Ubangijinka Shi ne Ya fi sanin wanda ya ɓace daga hanyarsa kuma Shi Ya fi sanin wanda ya shiriya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mushirikai waɗanda ba su yi imani da ranar lahira ba suna kiran mala’iku da sunan mata, domin a cewarsu su ‘ya’yan Allah ne mata, alhalin ba haka abin yake ba, suna faɗar waɗannan maganganun ne da jahilci ba da wani ilimi da suka dogara da shi ba sai shaci-faɗi da tsantsar zato, zato kuwa ba ya wadatar da komai game da gaskiya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa ya yi watsi da duk wanda ya bijire wa ambaton Allah ya zamanto ba gaskiya ce a gabansa ba, ba ya da wata manufa sai son rayuwar duniya kaɗai; ba wani aiki da yake yi don lahirarsa, domin bai yi imani da ita ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, duk irin waɗancan munanan maganganun da mushirikai suke yi na kiran mala’iku da sunan mata da sanya duniya a gaba da mantawa da lahira su ne ƙololuwar iliminsu, wanda ya kasa kai su ga samun yaƙini da gano gaskiya da aiki da ita. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa cewa shi ne mafi sanin wanda ya ɓace ya bar hanyar gaskiya. Shi kuma ne ya fi ƙowa sanin wanda ya shirya ya kama hanyarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk abin da yake sama da wanda yake ƙasa yana ƙarƙashin mulkin Allah ne, don haka shi ne wanda ya wajaba bayi su bauta masa, domin samun kyakkyawan sakamakonsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da cikakken adalci, don haka ne yake saka wa mai laifi gwargwadon laifinsa. Yana kuma da cikakkiyar falala, don haka ne yake saka wa wanda ya yi kyakkyawan aiki da mafi kyan sakamako fiye da aikinsa.

3. Zunubai kashi biyu ne; akwai manya-manyan zunubai, akwai kuma ƙanana.

Duk wani zunubi da aka sanya wa uƙubar haddi a duniya ko Allah da Manzonsa suka la'anci mai aikata shi, ko Allah ya ce zai yi hushi da shi, ko aka ambaci azabar wuta ga mai aikata shi, to duk waɗannan su ne manyan zunubai. Waɗanda kuma ba su shiga ɗaya daga waɗannan ba, to ƙananan zunubai ne'.

4. Yalwar gafarar Allah da rahamarsa ga bayinsa, ba don haka ba da ya hallaka duk waɗanda suke bayan ƙasa.

5. Allah shi ne mafi sanin yanayin ɗan'adam da ɗabi'arsa da raunin da ya halicce shi da shi, tun lokacin da ya halicci mutum na farko da lokacin da yake jariri a cikin mahaifiyarsa har ya fito duniya yana tattare da rauni da kasawa, to wannan shi ne ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kewaye shi da rahamarsa da gafararsa da afuwarsa da ihsaninsa.6. Hani game da tsarkake kai da yabon kai ba tare da wata hikima ta shari'a ba, domin taƙawa mahallinta zuciya ce, Allah kuwa shi ya fi kowa sanin abin da yake cikin zuciyar mutum.

Suratun Najm (31-32)

وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ لِيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ أَسَٰٓـُٔواْ بِمَا عَمِلُواْ وَيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ أَحۡسَنُواْ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٣١ ٱلَّذِينَ يَجۡتَنِبُونَ كَبَٰٓئِرَ ٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡفَوَٰحِشَ إِلَّا ٱللَّمَمَۚ إِنَّ رَبَّكَ وَٰسِعُ ٱلۡمَغۡفِرَةِۚ هُوَ أَعۡلَمُ بِكُمۡ إِذۡ أَنشَأَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ وَإِذۡ أَنتُمۡ أَجِنَّةٞ فِي بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمۡۖ فَلَا تُزَكُّوٓاْ أَنفُسَكُمۡۖ هُوَ أَعۡلَمُ بِمَنِ ٱتَّقَىٰ ٣٢

31. Kuma abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa na Allah ne, don Ya saka wa waɗanda suka munana da irin abin da suka aikata, Ya kuma saka wa waɗanda suka kyautata da mafi kyan sakamako.

32. (Su ne) waɗanda suke nisantar manya-manyan zunubai da munanan ayyukan sabo, sai dai 'yan ƙananan zunubai. Lalle Ubangijinka Mayalwacin gafara ne. Shi ne Ya fi sanin ku, tun sanda Ya halicce ku daga ƙasa, sai ga ku kun zama 'yan tayi a cikin cikin iyayenku mata; to kada ku tsarkake kanku; Shi ne Ya fi sanin wanda ya fi taƙawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi kaɗai ne mamallakin duk abin da yake cikin sammai da ƙasa, domin dukkansu halittarsa ne kuma bayinsa ne, shi ne kuma mai gudanar da su yadda ya ga dama. Yana zartar musu da ƙaddararsa da hukuncinsa da shari'arsa, yana umartar su ya hana su, don ya saka wa waɗanda suka munana ayyukansu da irin abin da suka cancanta na azaba, ya kuma saka wa muminai waɗanda suka kyautata ayyukansu da mafi kyan sakamako, shi ne gidan Aljanna.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta muminai masu kyawawan ayyuka da cewa su ne waɗanda suke nisantar manya-manyan zunubai da munanan ayyukan sabo, sai 'yan ƙananan zunubai waɗanda suke samun gafara a kansu, saboda sun kauce wa manyan laifuka sun kuma yawaita ayyukan ɗa'a; Allah yana yi musu gafarar ne saboda shi mai yalwar gafara ne, ba don haka ba da ya azabtar da mutane da yawa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Ban ga wani abu mai kama da *'lamamu*' ba kamar abin da Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Lalle Allah ya rubuta wa ɗan'adam rabonsa daga zina zai riske shi babu makawa; zinar ido shi ne kallo; zinar harshe kuma furuci; rai kuma sai ya yi buri ya yi sha'awa; farji kuma sai ya gaskata hakan ko ya ƙaryata shi." [Bukhari #5243 da Muslim #2657].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa 'yan'adam cewa, ya fi su sanin kawunansu da halayensu da abin da za su iya da wanda ba za su iya ba da ƙarfinsu da rauninsu, domin shi ne ya halicci

babansu Annabi Adamu daga ƙasa, da kuma lokacin da suke ‘yan tayi a cikin cikkunan iyayensu mata, sannan aka riƙa halittar su mataki-mataki, babu abin da bai sani ba game da su a waɗannan lokuta, don haka bai dace da su ba su riƙa tsarkake kawunansu suna siffanta kansu da taƙawa da tsoron Allah, domin shi Allah shi ne ya fi sanin mai taƙawa a cikin bayinsa.

An karɓo daga Zainab ‘yar Ummu Salama (Allah ya ƙara mata yarda) cewa, an sa mata suna Barra (watau mai biyayya) sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kada ku tsarkake kawunanku, Allah shi ne ya fi sanin masu biyayya daga cikinku.” [Muslim #2142].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Sunan Juwairiyya na farko Barra, sai Manzon Allah (ﷺ) ya canza mata shi zuwa Juwairiyya. Ba ya so ya ji ana cewa ya fito daga wajen Barra.” [Muslim #2140].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya zamanto ba ɗabi’arsa ce kyautatawa ba, to ko da ya yi ƙoƙarin yin wani abu na kyautatawa kaɗan ba zai iya ɗorewa a kai ba, zai dawo ya yi rowa ya hana.

2. Babu wanda ya san gaibu sai Allah kaɗai.

3. Duk littattafan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar sun tabbatar da cewa, kowane mutum yana cancantar aikinsa ne kawai, kuma ba wani rai da zai ɗauki laifin wani.

4. Tabbatar da Kudurar Allah a kan tashin matattu don yi musu hisabi da sakamako.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai yin yadda ya ga dama da ɗan’adam, shi ne yake sa shi farin ciki ko ya sa shi baƙin ciki, domin shi ne mahaliccin abubuwan da suke haifar da haka, ɗan’adam ba shi da wani iko nasa shi kaɗai a kansu. Wannan yana nuna cewa wajibi ne bawa ya koma ga Allah, ya yi masa biyayya, don ya ƙaddara masa abin da zai faranta masa rai ya raba shi da abin da zai baƙanta masa rai.

6. Ni’imomin da Allah yake yi wa bayinsa koyaushe suna da yawa waɗanda ya kamata mai hankali ya lura da su, ya yi imani da Ubangijinsa, ya bauta masa kada ya haɗa komai da shi.

Suratun Najm (33-55)

أَفَرَءَيْتَ ٱلَّذِى تَوَلَّىٰ ﴿٣٣﴾ وَأَعْطَىٰ قَلِيلًا وَأَكْدَىٰٓ ﴿٣٤﴾ أَعِندَهُۥ عِلْمُ ٱلْغَيْبِ فَهُوَ يَرَىٰٓ ﴿٣٥﴾ أَمْ لَمْ يُنَبَّأْ بِمَا فِى صُحُفِ مُوسَىٰ ﴿٣٦﴾ وَإِبْرَٰهِيمَ ٱلَّذِى
وَفَّىٰٓ ﴿٣٧﴾ أَلَّا تَزِرُ وَازِرَةٌ وِزْرَ أُخْرَىٰ ﴿٣٨﴾ وَأَن لَّيْسَ لِلْإِنسَٰنِ إِلَّا مَا سَعَىٰ ﴿٣٩﴾ وَأَنَّ سَعْيَهُۥ سَوْفَ يُرَىٰ ﴿٤٠﴾ ثُمَّ يُجْزَىٰهُ ٱلْجَزَآءَ ٱلْأَوْفَىٰ ﴿٤١﴾ وَأَنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ
ٱلْمُنتَهَىٰ ﴿٤٢﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَضْحَكَ وَأَبْكَىٰ ﴿٤٣﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَمَاتَ وَأَحْيَا ﴿٤٤﴾ وَأَنَّهُۥ خَلَقَ ٱلزَّوْجَيْنِ ٱلذَّكَرَ وَٱلْأُنثَىٰ ﴿٤٥﴾ مِن نُّطْفَةٍ إِذَا تُمْنَىٰ ﴿٤٦﴾ وَأَنَّ عَلَيْهِ
ٱلنَّشْأَةَ ٱلْأُخْرَىٰ ﴿٤٧﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَغْنَىٰ وَأَقْنَىٰ ﴿٤٨﴾ وَأَنَّهُۥ هُوَ رَبُّ ٱلشِّعْرَىٰ ﴿٤٩﴾ وَأَنَّهُۥٓ أَهْلَكَ عَادًا ٱلْأُولَىٰ ﴿٥٠﴾ وَثَمُودَا۟ فَمَآ أَبْقَىٰ ﴿٥١﴾ وَقَوْمَ نُوحٍ مِّن قَبْلُ ۖ
إِنَّهُمْ كَانُوا۟ هُمْ أَظْلَمَ وَأَطْغَىٰ ﴿٥٢﴾ وَٱلْمُؤْتَفِكَةَ أَهْوَىٰ ﴿٥٣﴾ فَغَشَّىٰهَا مَا غَشَّىٰ ﴿٥٤﴾ فَبِأَىِّ ءَالَآءِ رَبِّكَ تَتَمَارَىٰ ﴿٥٥﴾

33. Ka ba ni labarin wanda ya ba da baya.

34. Ya kuma bayar da dukiya kaɗan kuma ya yi rowa.

35. Shin yana da ilimin gaibu ne don haka yana ganin (komai)?

36. Ko ba a ba shi labarin abin da yake cikin takardun Musa ba ne?

37. Da kuma Ibrahimu wanda ya cika alƙawari?

38. Cewa: “Wani rai ba ya ɗaukar nauyin laifin wani.

39. “Kuma mutum bai mallaki wani sakamako ba sai na abin da ya aikata.

40. “Kuma lalle aikin nasa ba da daɗewa ba za a gan shi.

41. “Sannan a saka masa da cikakken sakamako.

42. “Lalle kuma zuwa ga Ubangijinka ne makoma.

43. “Kuma lalle Shi ne Ya sa a yi dariya, kuma Ya sa a yi kuka.

44. “Kuma lalle Shi ne Ya kashe kuma Ya raya.

45. “Kuma lalle Shi ne Ya halicci dangi biyu namiji da mace.

46. “Daga maniyyi yayin da ake zuba shi.

47. “Kuma lalle Ya ɗora wa kansa sake tashin matattu.

48. “Lalle kuma Shi ne Ya wadata, Ya kuma yalwata.

49. “Kuma lalle Shi ne Ubangijin tauraron nan *Shi’ira*.

50. “Lalle kuma Ya hallakar da Adawa na farko.

51. “Da kuma Samudawa, don haka bai bar saura ba.

52. “Da mutanen Nuhu tun kafin su; lalle su sun kasance su ne mafiya zalunci kuma mafiya ɗagawa.

53. “Da waɗanda aka kife (mutanen Luɗu, Allah) ya ƙasƙanta su.

54. “Sannan abin da ya lulluɓe su (na azaba) ya lulluɓe su.”

55. To (kai ɗan’adam) da waɗanne ni’imomin Ubangijinka kake jayayya?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan halin wanda ake umartar sa da kaɗaita Allah da bautar sa amma sai ya bijire bayan da ya nuna kusantar sa.
Abdurrahman ɗan Zaid yana cewa: Wannan ayar ta sauka ne game da wani mutum da ya musulunta sai wani kafiri ya riƙa aibanta shi yana cewa, ya tabka abin kunya, domin ya yarda ya bar addininsa na iyaye da kakanni ya dawo yana sukan su, yana ganin su ‘yan wuta. Sai wannan mutum ya nuna wa wannan kafiri cewa shi fa yana jin tsoron azabar Allah. Sai kafirin ya ce: “Ka ba ni wasu maƙudan kuɗi ni kuma zan ɗauke maka duk wata azaba da za ta hau kanka.” Sai ya ba shi wani abu na dukiya, sai ya nemi ya ƙara masa,

amma sai ya ji nauyin ya ƙara masa, sannan ya ɗan ƙara masa kaɗan. Sai kafirin ya rubuta game da shi ya kafa shaidu a kai. [Ibn Jariri, Tafsir Juzu'i na 22, shafi na 72].
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyi yake faɗa wa Manzon Allah wannan mummunan hali da wannan mutum ya faɗa cikinsa wanda har ya kai shi ga ƙara bijire wa Musulunci bayan da farko ya ɗan kusance shi. Ya yi alƙawarin zai bayar da wani abu na dukiyarsa don wani ya ɗauke masa azabar Allah a ranar alƙiyama, sai daga baya kuma ya hana. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci wannan kafirin da cewa, ya san gaibu ne da har yake faɗar zai iya ɗauke wa wani azabar Allah? Ko kuma dai ƙarya ce kawai yake yi wa Allah?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalinsa da cewa, shin ba a sanar da shi dokar Allah da ya saukar a cikin littattafan farko ba? Dokar da ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da wadda take cikin littattafan Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya cika duk wani umarni na Allah? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana waɗannan dokoki nasa da cewa:
Na farko, wani rai ba ya ɗaukar laifin wani. Kowa za a hukunta shi da abin da ya aikata ba abin da wani ya aikata ba.

An karɓo daga Abu Risma (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mun tafi tare da babana wurin Manzon Allah (ﷺ) sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa babana: "Wannan ɗanka ne?" Sai ya ce: "E, na rantse da Ubangijin Ka'aba." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ka tabbatar?" Sai ya ce: "Ka zama shaida a kan haka." Ya ce: Sai Manzon Allah (ﷺ) ya yi murmushi saboda yadda nake da tsananin kama da mahaifina amma duk da haka yana rantsuwa a kan ni ɗansa ne. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "To ka sani lalle ba za a kama shi da laifinka ba, kai ma ba za a kama ka da laifinsa ba." Sannan Manzon Allah (ﷺ) ya karanta faɗar Allah: "Wani rai ba zai ɗauki laifin wani ba." [Dubi, Ahmad #7109 da Abu Dawud #4495].

Na biyu, mutum ba shi da wani sakamako sai na aikinsa da ya yi. Watau bai cancanci ya nemi a ba shi sakamako ba sai a kan aikinsa. Wannan ba ya hana ya amfana da addu'ar wani gare shi ko sadakar 'ya'yansa da za su yi masa da sauran abubuwan da nassoshi suka zo da su. [Dubi, Al-Kinnauji, *Fathul Bayan*, Juzu'i na 13, shafi na 271-273].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan mutum ya mutu to aikinsa ya yanke sai na abubuwa uku, sadaka mai gudana, ko ilimin da ake amfana da shi, ko wani yaro nagari da zai riƙa yi masa addu'a." [Muslim #1631].
Na uku, lalle za a nuna wa mutum aikinsa a ranar alƙiyama, ya gan shi a rubuce a cikin takardun ayyukansa.
Na huɗu, lalle za a yi masa cikakken sakamako a kan dukkan ayyukansa ba tare da an tauye masa komai ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa makomar bayinsa duka bayan mutuwarsu zuwa gare shi ne, don haka duk tafiyar kowa da komai zuwa wurinsa za ta tuƙe ta ƙare.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake jan hankalin ɗan'adam a kan ya lura da wasu al'amura da suke wakana a rayuwarsa waɗanda dukkansu aikin Allah ne shi kaɗai:
Na farko, shi ne wanda ya sa a yi dariya ya kuma sa a yi kuka, watau shi ne yake kimsa farin ciki ga wanda ya ga dama har ya sa shi darawa saboda murna; shi kuma ne yake jefa baƙin ciki ga wanda ya ga dama har ya sa shi kuka.
Na biyu, shi ne mai kashe masu rai a nan duniya, ya kuma tashe su a lahira domin yi musu hisabi, kamar yadda shi ne ya samar da duk wani mai rai daga babu ya busa masa rai, sannan yake karɓar ransa bayan ajalinsa ya zo.
Na uku, shi ne ya halicci mutum nau'i biyu, namiji da mace daga maniyyi da ake zuba shi a mahaifa. Wannan duka yana nuna cikar Kudurarsa da Kaɗaitakarsa, don haka babu abin da yake gagararsa, saboda

haka ya tabbatar da cewa, shi ne mai ikon sake dawo da halittu bayan mutuwa domin yi musu hisabi da sakamako.
Na huɗu, shi ne ya ba wa wanda ya ga dama wadata, ya mallaka masa dukiya irin wadda ya ga dama, ya kuma yalwata wa bayinsa dukiyoyi iri-iri waɗanda suke mallaka domin amfaninsu na yau da kullum.
Na biyar, shi ne Ubangijin tauraron *Shi'ira*. Wannan wani tauraro ne mai tsananin haske da ke cikin taurarin burujin *Jauza'u*. Wasu ƙabilu na Larabawa a jahiliyya, kamar ƙabilar Khuza'atu sun riƙa bauta masa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, taurari ba su da wani tasiri, su ma bayin Allah ne, Mahaliccinsu shi ne Allah, shi kaɗai ya cancanta a bauta masa.
Na shida, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, shi ne ya hallaka Adawa na farko, watau mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da suka dage a kan kafircinsu, suka ƙaryata Manzonsu Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da iska mai tsananin ƙarfi ta hallaka su baki ɗaya. Hakanan shi ne ya hallaka Samudawa mutanen Annabi Salihu, yayin da suka ƙaryata Manzonsu Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka soke taguwarsa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su gaba ɗayansu bai bar ko mutum ɗaya ba. Hakanan shi ne ya hallaka mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) tun kafin zuwan Adawa da Samudawa. Mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kuwa sun fi tsananin kafirci da ɗagawa a bayan ƙasa fiye da Adawa da Samudawa, domin sai da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zauna a cikinsu tsawon shekara dubu ba hamsin yana musu wa'azi amma sai 'yan tsiraru ne suka yi imani da shi.
Hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne wanda ya yi ƙoli-ƙoli da garuruwan mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sannan ya jefo su ƙasa ya kifar da su, ya bi su da ruwan duwatsu har azaba mai girma ta lulluɓe su ta ko'ina, suka hallaka baki ɗaya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana butulcin ɗan'adam kafiri mai jayayya da Kudurar Allah da Kaɗaitakarsa bayan ɗimbin ni'imomi da ya yi masa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye shi da waɗanne ni'imomin ne na Ubangijinsa yake jayayya, ya ƙi ɗaukar izina da wa'azi?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rashin wa'azantuwa da abin da ya gabata na hallaka al'ummun farko siffa ce daga cikin siffofin kafirai.
2. Annabi (ﷺ) ba shi ne farau a cikin manzanni ba. Manzannin Allah da dama sun gabace shi.

3. Tabbatar da kusantowar tashin alƙiyama saboda bayyanar wasu alamominta, kamar aiko da Annabi Muhammadu (ﷺ).

4. Babu wanda ya san lokacin zuwan ranar alƙiyama sai Allah shi kaɗai.

5. Yin izgili yayin da ake karanta Alƙur'ani da rashin ɗaukar wa'azozinsa ko tasirantuwa da ayoyinsa ɗaya ne daga cikin siffofin kafirai.

Suratun Najm (56-62)
هَٰذَا نَذِيرٞ مِّنَ ٱلنُّذُرِ ٱلۡأُولَىٰٓ ٥٦ أَزِفَتِ ٱلۡأٓزِفَةُ ٥٧ لَيۡسَ لَهَا مِن دُونِ ٱللَّهِ كَاشِفَةٌ ٥٨ أَفَمِنۡ هَٰذَا ٱلۡحَدِيثِ تَعۡجَبُونَ ٥٩ وَتَضۡحَكُونَ وَلَا تَبۡكُونَ ٦٠
وَأَنتُمۡ سَٰمِدُونَ ٦١ فَٱسۡجُدُواْ لِلَّهِ وَٱعۡبُدُواْ ٦٢

56. Wannan mai gargaɗi ne daga irin masu gargaɗin farko.

57. Mai kusantowa ta kusanto (watau alƙiyama).

58. Ba wani mai bayyana lokacinta in ban da Allah.

59. Yanzu game da wannan zancen ne kuke mamaki?

60. Kuke kuma dariya ba kwa yin kuka?

61. Alhali kuna cikin gafala?

62. To ku yi sujjada ga Allah ku kuma bauta (masa).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai cewa Manzon Allah Muhammadu ɗan Abdullahi wanda ya aiko musu ɗaya ne daga cikin tarin manzanni na farko da ya aika zuwa ga mutanensu, don haka ba shi ne farau ba, abin da kuma ya zo da shi na gaskiya shi ne dai abin da sauran manzannin Allah suka zo wa mutanensu da shi, to don mene ne suke jayayya da shi a kan haka?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, alƙiyama ta kusanto, babu kuma mai iya bayanin lokacin zuwanta, ko mai iya kawar da abin da za ta zo da shi na narko ga kafirai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna kakabin irin yadda kafirai suke mamakin cewa Alƙur'ani daga Allah yake. Maimakon su yi imani da shi su wa'azantu lokacin da ake karanta musu ayoyinsa sai su riƙa dariya suna izgili da shi, ba sa kuka yayin jin wa'azuzzukansa, sukan ma shagalta ne su yi watsi da shi. Sai a ƙarshen wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su yi sujjada ga Allah shi kaɗai su bauta masa tare da tsarkake shi wajen bauta.

An karƀo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Annabi (ﷺ) ya karanta *'Suratun Najm*i' ya yi sujjada, sai Musulmi da mushirikai da aljannu da sauran mutane duk suka yi sujjada tare da shi." [Bukhari #6482 da Muslim #2283].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da kusantowar alƙiyama, saboda bayyanar wasu alamominta, kamar tsagewar wata gida biyu.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Kuraishawa manya-manyan ayoyi waɗanda za su sanya mutum ya ba da gaskiya, masu kuma tabbatar da ingancin abin da Manzo (ﷺ) ya zo musu da shi da gaskiyarsa. Daga cikin waɗannan ayoyi, Kuraishawa sun nemi Manzon Allah (ﷺ) ya nuna musu wata mu'ujiza wadda za ta tabbatar da manzancinsa, sai ya nuna wata, nan take suka ga ya rabu gida biyu da izinin Allah; tsagi ɗaya a kan dutsen Abu Kubais, ɗaya tsagin kuma a kan dutsen Ku'aiƙi'an. Bayan mushirikai sun ga wannan babbar ayar da ba a taɓa ganin irin ta ba, ba a kuma taɓa jin labarin kwatankwacinta ba, amma kuma sai suka ci gaba da kafircinsu, suka ƙaryata ta, suka ce sihiri ne. Don haka kafircin mushirikai bai zamanto saboda rashin ganin wata aya ba ne, a'a, son zuciya ne kawai da taurin kai.

3. Duk wanda zai ƙi gaskiya, to dole ne a same shi yana bin son zuciya.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai ɗora wa Manzonsa (ﷺ) nauyin kimsa shirya a cikin zukatan mutanensa ba. Abin da yake kansa kawai shi ne isar da saƙon Allah.

5. Tsananin ranar alƙiyama ga kafirai.

54-Suratul Kamar

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da sunan '*Suratul Kamar*' kamar yadda ya zo a cikin *Mus'hafi* da *Jami'ut Tirmizi*.
Magabata sukan kira ta da suna: '*Suratu iƙtarabatis Sa'a*', kamar yadda ya zo a hadisin Abu Waƙid Al-Laisi. [Dubi, Muslim #891 da Ahmad #21911].
An kuma kira ta ne da wannan suna saboda a farkonta an yi bayanin tsagewar wata a zamanin Annabi (ﷺ).

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai suna ganin Sura ce *Makkiyya* dukkanta.

3. Jerin Saukarta
Ita ce Sura ta talatin da bakwai (37) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratuɗ Ɗariƙ*' kafin '*Suratu Sad* '.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta hamsin da biyar ne (55) babu saɓani a kan haka.

5. Dalilin Saukarta
An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Wata ya tsage a zamanin Manzon Allah (ﷺ), sai Kuraishawa suka ce: "Wannan sihiri ne na ɗan Abu Kabsha." (Suna nufin Manzon Allah (ﷺ)). Sai suka ce wa junansu: "Ku saurara ku ji labarin da matafiya za su zo muku da shi, domin ai Muhammadu ba zai iya sihirce mutane gaba ɗaya ba." Da matafiya suka iso Makka sai Kuraishawa suka tambaye su, sai suka ce musu: "E, lalle mun gan shi." (watau yayin da ya tsage biyu). Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan Surar." [Al-Baihaƙi, *Dala'ilun Nubuwwa*, Juzu'i na 2, shafi na 266].

6. Babban Jigonta:
Bayanin ayoyin Allah da makomar masu ƙaryata su, da kuma yadda azabar Allah take kasancewa ga masu musu da jayayya da manzannin Allah.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Girman kai da mushirikai suka nuna na rashin imani da ayoyi bayyanannu.
• Tunatar da mushirikai irin abin da ya faru ga al'ummun da suka gabace su, waɗanda suka ƙaryata annabawansu, da tsoratar da su cewa, su ma irin wannan azabar za ta iya auka musu don ba su fi kafiran farko da komai ba.
• Yi musu gargaɗi game da yaƙin da za su fuskanta wanda za a karya su a cikinsa, sannan azabar da take jiran su a lahira ta fi tsanani.

• Nusantar da su cewa, Allah yana sane da duk ayyukansu, kuma zai yi musu sakayya a kansu kamar yadda zai saka wa masu taƙawa da kyakkyawan sakamako.

Suratul Kamar (1-8)

ٱقۡتَرَبَتِ ٱلسَّاعَةُ وَٱنشَقَّ ٱلۡقَمَرُ ۝١ وَإِن يَرَوۡاْ ءَايَةٗ يُعۡرِضُواْ وَيَقُولُواْ سِحۡرٞ مُّسۡتَمِرّٞ ۝٢ وَكَذَّبُواْ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهۡوَآءَهُمۡۚ وَكُلُّ أَمۡرٖ مُّسۡتَقِرّٞ ۝٣ وَلَقَدۡ جَآءَهُم
مِّنَ ٱلۡأَنۢبَآءِ مَا فِيهِ مُزۡدَجَرٌ ۝٤ حِكۡمَةُۢ بَٰلِغَةٞۖ فَمَا تُغۡنِ ٱلنُّذُرُ ۝٥ فَتَوَلَّ عَنۡهُمۡۘ يَوۡمَ يَدۡعُ ٱلدَّاعِ إِلَىٰ شَيۡءٖ نُّكُرٍ ۝٦ خُشَّعًا أَبۡصَٰرُهُمۡ يَخۡرُجُونَ
مِنَ ٱلۡأَجۡدَاثِ كَأَنَّهُمۡ جَرَادٞ مُّنتَشِرٞ ۝٧ مُّهۡطِعِينَ إِلَى ٱلدَّاعِۖ يَقُولُ ٱلۡكَٰفِرُونَ هَٰذَا يَوۡمٌ عَسِرٞ ۝٨

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Alƙiyama ta kusanto, wata kuma ya tsage.

2. Idan kuma suka ga wata aya sai su kau da kai kuma su ce: “Wannan sihiri ne ƙaƙƙarfa.”

3. Suka kuma ƙaryata, suka bi soye-soyen zukatansu. Kowane al’amari kuwa (na alheri ko na sharri) mai tabbata ne.

4. Haƙiƙa kuma wasu labarai waɗanda tsawatarwa take cikinsu sun zo musu.

5. Hikima ce mai kaiwa matuƙa, sai dai kuma gargaɗin ba ya amfanarwa.

6. Saboda haka ka rabu da su. A ranar da mai kira zai yi kira zuwa ga wani abu na ƙi a rai.

7. Idanuwansu suna a ƙasƙance suna fitowa daga ƙaburbura, kai ka ce su farin ɗango ne masu bazuwa.

8. Suna gaggawa zuwa ga mai kiran; kafirai za su riƙa cewa: “Wannan rana ce mai tsanani.”

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tsoratarwa cewa alƙiyama ta kusanto, wata kuma ya tsage, watau a zamanin Manzon Allah (ﷺ) wanda mushirikai suka gane wa idanunsu, amma sai suka yi ƙememe suka ƙi yarda da gaskiyar Annabi (ﷺ), suka ma tuhume shi da cewa, sihiri ne ya yi musu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, su waɗannan mushirikai ba gaskiya suke nema ba, jayayya kawai suke so, domin kuwa da a ce za su ga kowace aya da dalili mai ƙarfi a kan gaskiyar Manzon Allah (ﷺ), to da sun bijire sun ƙi yarda da shi har ma su ce, ai abin da suka gani wani ƙaƙƙarfan sihiri ne kuma zai gushe ba da jimawa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan mushirikan manufarsu ba ita ce ganin gaskiya su bi ta ba, a’a, buƙatarsu kawai ita ce su ƙaryata duk abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da shi na gaskiya, su bi son zuciyarsu, domin da gaskiya suke so da sun yi imani bayan sun ga ƙarfafan dalilai da idanuwansu. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da su cewa kowane al’amari na alheri ko na sharri mai tabbata ne a ranar alƙiyama inda kowa zai ga abin da ya kasance a kansa na gaskiya ko na ƙarya. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, waɗannan mutane ba neman gaskiya suke yi ba, domin kuwa labaran al’ummun da suka gabata waɗanda Allah ya hallaka su saboda kafircinsu da zaluncinsu ya zo musu, to da gaskiya ce a gabansu da wannan ya ishe su wa’azi da tsoratarwa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, abin da ya zo musu cikakkiyar hikima ce don kafa musu hujja da janyo hankulansu, to amma gargaɗi ba ya amfanar da mutanen da ba su yi imani da Allah da ranar lahira ba.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da cewa idan waɗannan mutane sun ƙi su shiriya, to ya yi watsi da su ya jira zuwan ranar da mala'ika mai busa a ƙaho zai yi kira zuwa ga wani mummunan al'amari wanda halittu ba su taɓa ganin irinsa ba, watau lokacin da matattu za su fito daga ƙaburburansu, idanunsu a ƙasƙance, su nufi wurin tsayuwa da gaggawa a kuma warwatsu kamar farin ɗango saboda yawansu. Za su yi ta gaggawa zuwa ga mai kiran don amsa kiransa, a nan ne kafirai za su ga gaskiyar abin da ake tsoratar da su shi, za su tabbatar da cewa, wannan rana ce mai tsanani da wahala a gare su, saboda sun san abin da suka shuka ba mai kyau ba ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zama bawan Allah babban matsayi ne a wurin Allah, shi ya sanya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan siffanta annabawansa da bauta gare shi.

2. Jifan mutanen kirki masu ƙoƙarin kawo gyara cikin al'umma da miyagun siffofi ko kiran su da sunayen banza, tsohuwar sara ce ta kafirai tun zamanin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) farkon manzannin da Allah ya aiko duniya.

3. Halaccin yi wa kafiri mummunar addu'a yayin da ya doge a kan kafircinsa ya kuma addabi muminai.

4. Taimakon Allah ga manzanninsa da salihan bayinsa sunnarsa ce tun da jimawa.

5. Hikimar sauƙaƙe karatun Alƙur'ani da haddarsa da fahimatarsa shi ne wa'azantuwa da ayoyinsa.

Suratul Kamar (9-17)

۞ كَذَّبَتۡ قَبۡلَهُمۡ قَوۡمُ نُوحٖ فَكَذَّبُواْ عَبۡدَنَا وَقَالُواْ مَجۡنُونٞ وَٱزۡدُجِرَ ٩ فَدَعَا رَبَّهُۥٓ أَنِّي مَغۡلُوبٞ فَٱنتَصِرۡ ١٠ فَفَتَحۡنَآ أَبۡوَٰبَ ٱلسَّمَآءِ بِمَآءٖ مُّنۡهَمِرٖ ١١ وَفَجَّرۡنَا ٱلۡأَرۡضَ عُيُونٗا فَٱلۡتَقَى ٱلۡمَآءُ عَلَىٰٓ أَمۡرٖ قَدۡ قُدِرَ ١٢ وَحَمَلۡنَٰهُ عَلَىٰ ذَاتِ أَلۡوَٰحٖ وَدُسُرٖ ١٣ تَجۡرِي بِأَعۡيُنِنَا جَزَآءٗ لِّمَن كَانَ كُفِرَ ١٤ وَلَقَد تَّرَكۡنَٰهَآ ءَايَةٗ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ١٥ فَكَيۡفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ١٦ وَلَقَدۡ يَسَّرۡنَا ٱلۡقُرۡءَانَ لِلذِّكۡرِ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ١٧

9. Mutanen Nuhu sun ƙaryata kafin su (Kuraishawa), sai suka ƙaryata Bawanmu suka kuma ce, mahaukaci ne, aka kuma kyare (shi).

10. Sai ya roƙi Ubangijinsa (cewa): "Lalle an fi ƙarfina, sai Ka taimaka."

11. Sai Muka buɗe ƙofofin sama da ruwa mai kwararowa.

12. Muka kuma ɓuɓbugar da idanuwan ruwa daga ƙasa, sai ruwayen suka haɗu a bisa al'amarin da aka riga aka ƙaddara.

13. Muka kuma ɗauke shi a kan (jirgin ruwa) mai alluna da ƙusoshi.

14. Yana gudu a kan idonmu, don ya zama sakayya ga wanda aka kafirce wa (watau Nuhu).

15. Haƙiƙa kuma Mun bar (abin da ya faru) ya zama aya, to ko akwai mai wa'azantuwa?

16. To ƙaƙa azabata da gargaɗina suka kasance?

17. Haƙiƙa kuma Mun sauƙaƙe Alƙur'ani don tunasarwa da hadda, to ko akwai mai wa'azantuwa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) ne game da ƙaryata shi da mutanensa suke yi, da cewa al'ummun da suka gabace su ma sun ƙaryata manzanninsu kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara lissafa manzannin da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da mutanensa suka ƙaryata shi, lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aike shi gare su, har ma suka kira shi da mahaukaci, suka riƙa yi masa tsawa da cin zarafi iri-iri, har ta kai su ga yi masa barazanar kisa idan bai bar da'awarsa ba. Daga nan ne shi kuma ya roƙi Ubangijinsa cewa ya kawo masa ɗauki, domin mutanensa sun fi ƙarfinsa, sun ƙi yin imani da shi bayan ya shafe shekara dubu ba hamsin a cikinsu yana yi musu wa'azi. Ya roƙi Allah ya saukar musu da azabarsa wadda za ta hallaka su ba za ta bar ko mutum guda daga cikinsu ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa ya karɓi addu'arsa, don haka ya buɗe ƙofofin sama ruwa ya yi ta kwararowa babu ƙaƙƙautawa, Ya kuma ɓubbugo da idanuwan ruwa ta ƙasa ta ko'ina, sai ruwan sama da na ƙasa suka haɗe suka gama duniya bisa umarnin Allah da ya riga ya ƙaddara shi tun fil azal. Allah ya hallakar da mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ruwan Ɗufana gaba ɗayansu tare da dabbobinsu da dukiyoyinsu sai fa wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya ɗauki Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi da waɗanda suke tare da shi a cikin jirgin ruwa wanda aka ƙera da alluna da ƙusoshi, yana gudu a kan ruwa tare da kulawar Allah da lurarsa, domin wannan ya zamanto sakayya ga Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda mutanensa suka ƙaryata shi, suka kuma kafirce wa abin da ya zo musu da shi daga Allah.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan azaba da ya yi wa mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bar ta don ta zama aya da izina ga duk wani mai wa'azantuwa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin mushirikai a kan su lura su ga yadda azabarsa da gargaɗinsa ga mutanen Annabi Nuhu suka kasance.
Sai kuma Allah ya tabbatar da cewa, ya sauƙaƙe Alƙur'ani don a karanta shi a haddace shi a fahimce shi, domin ya zama wa'azi da tunatarwa, to shin ko akwai mai wa'azantuwa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk ƙarfin mutane da ci gabansu na rayuwar duniya, ba a bakin komai suke ba a wurin Allah, matuƙar sun kafirce masa sun zaɓi saɓa wa annabawansu.

2. Duk abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halitta yana iya zama rundunarsa wadda zai hallaka masu kafirce masa da ita. Kamar yadda yake iya mayar da abin da a zahirinsa ni'ima ce ya zama azabarsa da zai hallaka wanda ya so da ita, kamar yadda ya hallaka Adawa da iska.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya kwanakin nan takwas na hallakar da Adawa su zamanto kwanaki ne da suke cike da shu'umci gare su, saboda azabar da ke cikinsu, to amma a cikinsu ne kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da Annabi Hudu da jama'arsa muminai, ya ba su nasara a kan maƙiyansu, don haka su a wurinsu kwanaki ne masu albarka. Don haka babu wasu kwanaki na shu'umci a karan kansu kamar yadda wasu al'ummu suke zato har suke haramta wa kawunansu wasu ayyukan alheri a cikinsu.

Suratul Kamar (18-22)

كَذَّبَتْ عَادٌ فَكَيْفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ﴿١٨﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِيحًا صَرْصَرًا فِي يَوْمِ نَحْسٍ مُّسْتَمِرٍّ ﴿١٩﴾ تَنزِعُ ٱلنَّاسَ كَأَنَّهُمْ أَعْجَازُ نَخْلٍ مُّنقَعِرٍ ﴿٢٠﴾
فَكَيْفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ﴿٢١﴾ وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٍ ﴿٢٢﴾

18. Adawa sun ƙaryata (Annabinsu), to ƙaƙa azabata da gargaɗina suka kasance?

19. Lalle Mu Mun aiko musu da iska mai ƙarfi a ranar shu'umci mai zarcewa.

20. Tana tumɓuko mutane ta kayar su, kai ka ce su kututturan dabinai ne da aka tuttunɓuke.

21. To ƙaƙa azabata da gargaɗina suka kasance?

22. Kuma haƙiƙa Mun sauƙaƙe Alƙur'ani don tunatarwa, to ko akwai mai wa'azantuwa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake jan hankalin Larabawa mushirikai a kan su yi la'akari da azabarsa da gargaɗinsa ga Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) lokacin da suka ƙaryata shi suka doge a kan kafircinsu, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu wata iska mai tsananin sanyi a wani yini mai shu'umancin gaske wanda shu'umcinsa ba iya nan duniya ya tsaya ba; zai zarce ne yana bin su har zuwa lokacin shigarsu wutar Jahannama a ranar alƙiyama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan iskar da ya aika wa Adawa ta riƙa tumɓuke mutane daga doron ƙasa ta yi sama da su sannan ta kifo da su ta kawunansu su faɗo ƙasa a mace, idan mutum ya gan su kwankwance a ƙasa sai ya ga kamar kututturan dabino ne da aka daddatse su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake umartar mushirikai da su yi la'akari da tunani game da azabarsa da ya saukar wa Adawa da kuma gargaɗinsa da yake yi wa wasunsu na su ɗauki izina daga waɗancan mutane. Sai kuma ya tabbatar da cewa, ya sauƙaƙe Alƙur'ani wajen karatunsa da haddarsa da fahimtarsa don wa'azantuwa, to shin ko akwai mai wa'azantuwa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirai sun fake da kasancewar manzanninsu mutane ne irinsu sai suka ƙaryata su ba tare da wata hujja ba.

2. Rashin yardar kafirai da zaɓin Allah ga bayinsa da sanin inda ya dace ya ajiye manzancinsa, shi ne ya sanya su kafirce wa manzanninsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ba wa annabawansa mu'ujiza don ta zama jarraba ga mutanensu, sannan ta zama sanadiyyar saukar azabarsa gare su bayan sun kafirce mata.

4. Wanda ya aikata laifi da hannunsa da wanda ya umarce shi da wanda ya goyi baya, dukkansu idan azabar Allah ta zo za ta shafe su ne gaba ɗayansu.

Suratul Kamar (23-32)

كَذَّبَتْ ثَمُودُ بِٱلنُّذُرِ ﴿٢٣﴾ فَقَالُوٓاْ أَبَشَرًا مِّنَّا وَٰحِدًا نَّتَّبِعُهُۥٓ إِنَّآ إِذًا لَّفِي ضَلَٰلٍ وَسُعُرٍ ﴿٢٤﴾ أَءُلْقِيَ ٱلذِّكْرُ عَلَيْهِ مِنۢ بَيْنِنَا بَلْ هُوَ كَذَّابٌ أَشِرٌ ﴿٢٥﴾
سَيَعْلَمُونَ غَدًا مَّنِ ٱلْكَذَّابُ ٱلْأَشِرُ ﴿٢٦﴾ إِنَّا مُرْسِلُواْ ٱلنَّاقَةِ فِتْنَةً لَّهُمْ فَٱرْتَقِبْهُمْ وَٱصْطَبِرْ ﴿٢٧﴾ وَنَبِّئْهُمْ أَنَّ ٱلْمَآءَ قِسْمَةٌۢ بَيْنَهُمْ ۖ كُلُّ شِرْبٍ مُّحْتَضَرٌ ﴿٢٨﴾

فَنَادَوْاْ صَاحِبَهُمْ فَتَعَاطَىٰ فَعَقَرَ ﴿٢٩﴾ فَكَيْفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ﴿٣٠﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ صَيْحَةً وَٰحِدَةً فَكَانُواْ كَهَشِيمِ ٱلْمُحْتَظِرِ ﴿٣١﴾ وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٍ ﴿٣٢﴾

23. Samudawa sun ƙaryata gargaɗi.

24. Sannan suka ce: “Yanzu mutum ɗaya daga cikinmu ne za mu bi? To lalle idan mun yi haka, mun tabbata cikin ɓata da hauka.

25. “Yanzu (zai yiwu) a saukar masa da wahayi a tsakaninmu? A’a, shi dai maƙaryaci ne mai tsananin girman kai.”

26. A gobe lalle za su san wane ne maƙaryacin mai girman kai.

27. Lalle Mu Masu aiko taguwa ne don ta zama fitina a gare su, saboda haka ka saurara musu, kuma ka jure.

28. Kuma ka ba su labarin cewa ruwan sha an raba ne tsakaninsu (da ita taguwar); kowane akwai ranar shansa.

29. Sai suka kirawo (shaƙiyin) abokin nasu sai ya ɗauki (abin sara) sai ya sare ta.

30. To ƙaƙa azabata da gargaɗina suka kasance?

31. Lalle Mun aika musu da tsawa guda ɗaya, sai suka zamo kamar duddugar ciyawa a garken makiyayi.

32. Haƙiƙa kuma Mun sauƙaƙe Alƙur’ani don tunatarwa, to ko akwai mai wa’azantuwa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Kuraishawa cewa, Samudawa mutanen Annabi Salihu sun ƙaryata gargaɗin da Annabinsu ya yi musu, domin wai suna ganin cewa ta ƙaƙa za su bi wani mutum guda ɗaya irinsu wanda bai fi su da komai ba, suka tabbatar masa da cewa, lalle su har in sun yarda sun bi shi a haka, to tabbas sun tabka babban kuskure a rayuwarsu, sun kuma jefa kansu cikin hauka. Sannan suna mamakin cewa, ta yaya za a ware shi shi kaɗai a yi masa wahayi, su kuma ba a yi musu ba? Don haka suka yanke hukuncin cewa Annabi Salihu babban maƙaryaci ne mai girman kai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, ba da jimawa ba gobe za su san wane ne babban maƙaryaci mai girman kai tsakanin shi da su?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya fito wa da Samudawa taguwa daga wani falalen dutse kamar yadda suka nema, don ta zama jarraba a gare su, ya kuma umarci Annabinsa Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya saurara ya ga yadda za su yi wa wannan taguwa, su kuma ya ga yadda Allah zai yi da su, shi kuma ya ci gaba da haƙuri a kan cutarwarsu gare shi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya faɗa wa mutanensa cewa ruwan rijiyarsu na sha an raba musu shi ne tsakaninsu da wannan taguwar, kowannensu akwai ranarsa da zai sha ruwanta, watau yau gare su gobe ga taguwar, ba wanda zai halarci ranar wani tsakaninsu da ita.
To amma sai Samudawa suka kasa kiyaye wannan doka, har ma wasu daga cikinsu suka gana da junansu suka yanke shawarar su kashe taguwar Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kowa ya huta,

don haka sai suka kirawo shaƙiyyunsu suka umarce shi da wannan mugun aiki, shi kuma ya ɗauki takobinsa ya sare wannan taguwa, ya cika umarnin shugabanninsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mutanen Makka da su lura da yadda azabar Allah ta kasance ga mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da gargaɗinsa ga na bayansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya aika musu wata tsawa guda ɗaya wadda ta hallaka su gaba ɗayansu, suka wayi gari kamar duddugar ciyawa busassa a garken dabbobi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya sauƙaƙe Alƙur'ani wajen karatunsa da haddarsa da fahimtarsa don tunatarwa da wa'azi, to ko akwai mai wa'azantuwa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bayan sun ƙaryata duk gargaɗi da jan kunne da ya yi musu, domin Allah ba ya hallaka wata al'umma sai ya aiko mata mai gargaɗi.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da iyalansa, watau 'ya'yansa mata, in ban da matarsa wadda ta kasance cikin halakakku, domin ita ta fita daga sahun iyalansa saboda kafircinta.

3. Duk wani mai godiya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai tserar da shi daga azabar da ya saukar wa masu keta dokokinsa.

4. Jan hankalin Kuraishawa game da ci gaba da jayayya da Annabi (ﷺ) da suke yi, domin yin haka zai jawo musu azabar Allah kamar yadda ya faru ga mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

5. Duk waɗanda ake aikata laifuffuka a gaban idonsu suna da ikon su hana amma ba su hana ba har ma suka goyi bayan masu aikatawar, to duka sakamakonsu iri ɗaya ne. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jingina neman baƙin Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da lalata zuwa ga mutanensa gaba ɗaya, tare da cewa wasu ne daga cikinsu suka aikata haka ba duka mutanen garin ba, amma saboda yardarsu da goyon bayansu ga masu aikata laifin sai suka zama ɗaya.

Suratul Kamar (33-40)
كَذَّبَتْ قَوْمُ لُوطٍۭ بِٱلنُّذُرِ ﴿٣٣﴾ إِنَّآ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ حَاصِبًا إِلَّآ ءَالَ لُوطٍۖ نَّجَّيْنَٰهُم بِسَحَرٍ ﴿٣٤﴾ نِّعْمَةً مِّنْ عِندِنَاۚ كَذَٰلِكَ نَجْزِى مَن شَكَرَ ﴿٣٥﴾ وَلَقَدْ أَنذَرَهُم بَطْشَتَنَا فَتَمَارَوْا۟ بِٱلنُّذُرِ ﴿٣٦﴾ وَلَقَدْ رَٰوَدُوهُ عَن ضَيْفِهِۦ فَطَمَسْنَآ أَعْيُنَهُمْ فَذُوقُوا۟ عَذَابِى وَنُذُرِ ﴿٣٧﴾ وَلَقَدْ صَبَّحَهُم بُكْرَةً عَذَابٌ مُّسْتَقِرٌّ ﴿٣٨﴾ فَذُوقُوا۟ عَذَابِى وَنُذُرِ ﴿٣٩﴾ وَلَقَدْ يَسَّرْنَا ٱلْقُرْءَانَ لِلذِّكْرِ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٍ ﴿٤٠﴾

33. Mutanen Luɗu sun ƙaryata gargaɗi.

34. Lalle Mun aika musu da iska cike da duwatsu (ta hallaka su), sai dai iyalin Luɗu kaɗai Muka tserar da su a lokacin asuba.

35. (Wannan) ni'ima ce daga wurinmu. Kamar haka Muke saka wa wanda ya yi godiya.

36. Kuma haƙiƙa ya tsoratar da su irin damƙarmu, sai suka yi jayayya da gargaɗin (da ya yi musu).

37. Haƙiƙa kuma sun nemi baƙinsa da lalata, sai Muka shafe idanuwansu, (Muka ce da su): “Sai ku ɗanɗani azabata da gargaɗina.”

38. Haƙiƙa kuma azaba matabbaciya ta yi musu sammako da asuba.

39. Saboda haka ku ɗanɗani azabata da gargaɗina.”

40. Haƙiƙa kuma Mun sauƙaƙe Alƙur’ani don tunatarwa, to ko akwai mai wa’azantuwa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya labarta wa mushirikai cewa mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sun ƙaryata abin da Manzonsu Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi musu gargaɗi da shi, yayin da ya kira su zuwa ga bautar Allah shi kaɗai, ya yi musu kashedi da aikata shirka da mummunar alfasha ta neman maza, to amma sai suka ƙaryata shi, suka ci gaba da laifukan da suke yi, har zuwa lokacin da mala’iku suka baƙunci Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a gidansa a cikin kamannin mazaje. Mutanen Annabi Luɗu kuwa suka yunƙuro da nufin aikata alfasha da su. A nan ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci waɗannan mala’iku da su hallaka su gaba ɗayansu in ban da Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka yi imani da shi daga cikin ahlinsa, amma ban da matarsa wadda ita kam tana cikin kafirai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya aiko musu da iska mai cike da duwatsu waɗanda suka yi ta sauka a kansu bayan an kifar da garuruwansu, inda ilahirinsu suka hallaka sai dai iyalan Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) kaɗai, su ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tserar da su lokacin da ya umarce shi da ya fita da su tun kafin saukar wannan azabar a ƙarshen dare.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya kuɓutar da Annabi Luɗu da iyalansa daga azaba ne don yin ni’ima a gare su, kuma kamar haka ne yake sakayya ga duk wanda ya gode wa ni’imarsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi ta gargaɗin mutanensa game da wannan azabar ta Ubangiji, to amma sai suka ƙi ji, suka yi ta jayayya game da gargaɗin da yake yi musu suka ƙaryata shi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin yadda rashin kunyar mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ta yi tsamari har sai da suka kai ga neman sa da ya ƙyale su su yi lalata da baƙinsa, watau mala’ikun da Allah ya aiko masa, suka yunƙuro da ƙarfinsu suna so su cim ma biyan buƙatarsu, sai Allah ya shafe idanuwansu suka makance, don haka suka kasa shiga wurinsu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce musu, su ɗanɗani azabarsa da sakamakon bijire wa gargaɗinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya hallaka su lokacin da tabbatacciyar azabarsa ta yi musu sammako daidai lokacin asuba, saboda haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce musu su ɗanɗani azabarsa sakamakon gargaɗinsa da suka bijire wa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tabbatar da cewa, ya sauƙaƙe Alƙur’ani wajen karatunsa da haddarsa da fahimtarsa don tunatarwa, to shin ko akwai mai wa’azantuwa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai nuna cewa ya aika Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga al’ummar Kibɗawa mutanen ƙabilar Fir’auna ba, domin bai je don ya kai musu wata shari’a ba, sai dai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika shi ne zuwa ga Fir’auna da fadawansa waɗanda suke taya shi gudanar da mulkinsa na zalunci, domin su ba da damar a saki Banu Isra’ila da ake tsare da su bisa zalunci a kuma daina bautar da su, su kuma ba su damar fita tare da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga Misra. Don haka ne a nan kawai sai aka ce: "Gargaɗi ya zo wa dangin Fir’auna".

2. Tsananin damƙar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga waɗanda suka ƙaryata ayoyinsa.

Suratul Kamar (41-42)

وَلَقَدۡ جَآءَ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ ٱلنُّذُرُ ۝٤١ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا كُلِّهَا فَأَخَذۡنَٰهُمۡ أَخۡذَ عَزِيزٖ مُّقۡتَدِرٍ ۝٤٢

41. Kuma haƙiƙa gargaɗi ya zo wa mutanen Fir’auna.

42. Suka ƙaryata ayoyinmu dukkaninsu, sai Muka kama su irin kamu na Mabuwayi, Mai iko.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, gargaɗi iri-iri ya zo wa Fir’auna da mutanensa lokacin da ya aika musu Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Haruna (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ba su ayoyi bayyanannu da ƙarfafan dalilai waɗanda suka nuna wa Fir’auna da jama’arsa, amma sai suka ƙaryata su baki ɗaya, suka sa ƙafa suka shure su, sai Allah ya kama su da azabarsa, irin kamu na mabuwayi wanda ya fi ƙarfin komai, mai iko a kan komai, babu abin da yake gagarar sa, watau ya nutsar da Fir’auna da rundunarsa a cikin ruwa suka hallaka gaba ɗayansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa da kwantar musu da hankali da cewa nasara tana tare da su ba da jimawa ba.

2. Tabbatar da mu’ujizar Alƙur’ani yayin da ya ba da labarin cewa ba da jimawa ba za a karya rundunar kafiran Makka, sai ga shi hakan ya faru a yaƙin Badar shekara ta biyu bayan hijira.

3. Duk tsananin azabar duniya, to ta lahira ta fi ta tsanani.

Suratul Kamar (43-46)

أَكُفَّارُكُمۡ خَيۡرٞ مِّنۡ أُوْلَٰٓئِكُمۡ أَمۡ لَكُم بَرَآءَةٞ فِي ٱلزُّبُرِ ۝٤٣ أَمۡ يَقُولُونَ نَحۡنُ جَمِيعٞ مُّنتَصِرٞ ۝٤٤ سَيُهۡزَمُ ٱلۡجَمۡعُ وَيُوَلُّونَ ٱلدُّبُرَ ۝٤٥ بَلِ ٱلسَّاعَةُ مَوۡعِدُهُمۡ وَٱلسَّاعَةُ أَدۡهَىٰ وَأَمَرُّ ۝٤٦

43. Yanzu kafiranku (ku mutanen Makka) su ne suka fi waɗancan alheri, ko kuwa kuna da wata hanya ta kuɓuta ne a cikin littattafan da aka saukar?

44. A’a, suna dai cewa ne: “Mu jama’a ce wadda za ta ci nasara.”

45. To ba da daɗewa ba za a karya jama’ar tasu, su kuma su ba da baya.

46. A’a, alƙiyama ita ce lokacin yi musu azaba, alƙiyama kuwa ita ta fi bala’i, ta kuma fi ɗaci.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin kafirai masu ƙaryata Manzonsa (ﷺ) game da azabarsa da za ta iya sauka a kansu idan ba su yi imani ba, kamar yadda ta sauka a kan waɗancan al’ummu da ya ba su labarinsu. Domin bai kamata a ce suna zaton su sun fi ƙarfin azabar Allah ba, sai don in suna zaton ɗaya daga cikin abubuwa uku:
Na ɗaya, ko dai suna ganin su sun fi waɗancan kafiran na farko, tare da cewa ga su sun ƙaryata mafi darajar manzannin Allah kuma shugabansu Annabi Muhammadu (ﷺ). To idan suna ganin sun fi su matsayi ne a wurin Allah, to tana iya yiwuwa su tsira. To amma su ma sun san abin ba haka yake ba, in dai ba su zama mafi sharrinsu ba, to ba za su kasa zama daidai da su ba.

Na biyu, ko kuma ya zamanto Allah ya yi musu wani alƙawari ne a cikin littattafan da ya saukar wa annabawansa da cewa, su za su tsira daga azabarsa ko da kuwa sun ƙaryata Manzonsa. To su ma sun tabbatar da cewa, wannan bai faru ba.
Na uku, ko kuma suna ganin cewa suna da wani ƙarfi ne wanda za su yi nasara a kan duk wata azaba da za ta doso su. Tabbas ba su da ƙarfin da za su kare kansu daga azabar Allah.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba da jimawa ba zai tarwatsa taronsu ya karya lagon jama'arsu su juya a guje. Haka kuwa ya faru a yaƙin Badar inda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karya lagon kafiran Makka aka kashe manyansu da dama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, suna da wani lokaci da ya yi alƙawarin tattara su baki ɗaya don yi musu azaba, ita ce ranar alƙiyama, wadda rana ce mafi girman bala'i gare su kuma mafi tsanani, inda za su gamu da azabar da ta fi wadda suka gamu da ita a ranar Badar nesa ba kusa ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: A yaƙin Badar Manzon Allah (ﷺ) yana zaune a cikin wani ƙaramin tanti sai yake addu'a yana cewa: "Ya Allah, ina roƙon ka alƙawarin da ka yi min na cin nasara, ya Allah, in ka ga damar hallaka waɗannan muminan to ba za a sake bautar ka ba daga yau." Sai Abubakar (Allah ya kara masa yarda) ya kama hannunsa yana ce masa: "Addu'ar ta isa hakanan ya Manzon Allah, ka nuna nacinka ga Ubangijinka." Sai ya taso yana sanye da silkensa yana karanta faɗar Allah: "To ba da daɗewa ba za a karya jama'ar tasu, su kuma ba da baya. A'a, alƙiyama ita ce wa'adinsu, alƙiyama kuma ta fi bala'i kuma ta fi tsanani." [Bukhari #2915].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da Kaddarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cikin komai da ya halitta.

2. Bayanin cikar ikon Allah da girman Kudurarsa.

3. Cikar adalcin Ubangiji ta yadda ake rubuta ayyukan bayi ƙanana da manya, domin a yi musu sakamako gwargwadon aikin kowa ba tare da an zalunce su komai ba.

4. Bayanin girman sakamako na masu taƙawa a gidan Aljanna.

Suratul Kamar (47-55)
إِنَّ ٱلْمُجْرِمِينَ فِى ضَلَٰلٍ وَسُعُرٍ ﴿٤٧﴾ يَوْمَ يُسْحَبُونَ فِى ٱلنَّارِ عَلَىٰ وُجُوهِهِمْ ذُوقُوا۟ مَسَّ سَقَرَ ﴿٤٨﴾ إِنَّا كُلَّ شَىْءٍ خَلَقْنَٰهُ بِقَدَرٍ ﴿٤٩﴾ وَمَآ أَمْرُنَآ إِلَّا وَٰحِدَةٌ
كَلَمْحٍۭ بِٱلْبَصَرِ ﴿٥٠﴾ وَلَقَدْ أَهْلَكْنَآ أَشْيَاعَكُمْ فَهَلْ مِن مُّدَّكِرٍ ﴿٥١﴾ وَكُلُّ شَىْءٍ فَعَلُوهُ فِى ٱلزُّبُرِ ﴿٥٢﴾ وَكُلُّ صَغِيرٍ وَكَبِيرٍ مُّسْتَطَرٌ ﴿٥٣﴾ إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ فِى
جَنَّٰتٍ وَنَهَرٍ ﴿٥٤﴾ فِى مَقْعَدِ صِدْقٍ عِندَ مَلِيكٍ مُّقْتَدِرٍۢ ﴿٥٥﴾

47. Lalle masu manyan laifuka suna cikin ɓata da azabar wuta.

48. Ranar da za a ja su cikin wuta a kan fuskokinsu (a ce da su): "Ku ɗanɗani azabar wutar Saƙara."

49. Lalle Mu, kowane abu Mun halitta shi da ƙaddara.

50. Kuma al'amarinmu bai zamanto ba face kalma ɗaya kamar ƙiftawar ido.

51. Haƙiƙa kuma Mun hallakar da ire-irenku, to ko akwai mai wa'azantuwa?

52. Kuma kowane abu da suka aikata yana cikin littattafai.

53. Kowane ƙaramin abu da babba kuma suna nan a rubuce.

54. Lalle masu taƙawa suna cikin gidajen Aljanna da ƙoramu.

55. A mazauni na gaskiya a wurin Mai mulki, Mai iko.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, masu aikata manyan laifuka kamar shirka da sauran ayyukan saɓon Allah, suna cikin ɓata da barin gaskiya a nan duniya, suna kuma cikin azaba da wahala a ranar lahira. Ranar da mala'iku za su yi ta jan su a kan fuskokinsu a cikin wuta, a nuna musu matuƙar wulaƙanci da ƙaskanci ana kuma faɗa musu cewa su ɗanɗani azabar wutar Saƙara.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lalle komai a duniya ya halicce shi ne da ƙaddararsa wadda ta riga ta gabata, don ya san komai da komai, ya kuma rubuta shi a littafin Lauhul Mahfuzu, yana kuma faruwa ne da ganin damarsa da izininsa. Wannan kuwa aiki ne mai matuƙar sauƙi a wurinsa, don haka ya tabbatar da cewa, idan ya nufi faruwar wani abu to umarninsa kalma ɗaya ce kawai, watau ya ce wa abin nan 'kasance', kafin ƙiftawar ido kuwa ya kasance.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Mushirikan Kuraishawa sun zo suna jayayya da Manzon Allah (ﷺ) game da ƙaddara, sai faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta sauka inda yake cewa: "Ranar da za a ja su cikin wuta a kan fuskokinsu (a ce da su) ku ɗanɗani azabar wutar Saƙara. Lalle mu kowane abu mun halicce shi da ƙaddara." [Muslim #2656 da Tirmizi #3290 da Ahmad #9736].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake jan hankalin kafirai a kan su guji fushinsa (Mai tsarki da ɗaukaka), da cewa ya hallaka wasu kafirai irinsu masu taurin kai, to shin wannan bai ishe su wa'azi ba, su ma su ji tsoron kada irin haka ya faru da su?
Sannan ya kuma tabbatar da cewa, duk fa wani abu da bayinsa suke aikatawa yana nan a rubuce a cikin littattafan mala'iku masu tsaron su, babu abin da yake kuɓuce musu. Kuma duk wani aikinsu ko maganarsu ƙaramin abu da babba yana nan a rubuce a littattafansu na ayyuka da kuma Lauhul Mahfuzu, zai yi musu sakayya a kansu.
Sai kuma a ƙarshen Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon masu taƙawa da kiyaye dokokinsa da cewa suna cikin gidajen Aljanna na jin daɗi da ƙoramu masu gudana, a wani majalisi na gaskiya wanda babu maganar banza ko laifi a cikinsa a wurin Sarki mamallakin komai mai cikakken iko da babu abin da yake gagarar sa, zai kuma yi musu goma ta arziki da babu mai iya bayyana girmanta da daɗinta sai dai wanda ya gani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Farawa da ambaton girman ni'imar Alƙur'ani da darajarsa da Allah ya yi wa bayinsa mutane da aljanu baiwarta.

2. Yana daga cikin manyan rahamomin Allah yadda ya koyar da bawansa karatun Alƙur'ani ya ba shi fahimtar ma'anoninsa da hikimomin da ke cikinsa cikin sauƙi, domin duk wani alheri yana tattare da Alƙur'ani.

3. Halittar ɗan'adam cikin kyakkyawar kama da daidaito, wata babbar ni'imar Allah ce gare shi.

4. Wata babbar ni’imar Allah ga ɗan’adam ita ce, koyar da shi yadda zai yi bayanin abin da yake ransa ta hanyar furuci ko kuma rubutu, domin da wannan ne ɗan'adam ya bambanta da sauran halittun Allah masu yawa.

5. Yana daga cikin hikimomin halittar rana da wata da hore musu tafiya a cikin falakansu cikin tsari, shi ne don ɗan’adam ya samu damar lissafin shekaru da kuma kwanakin wata da su. Wannan ma wata babbar rahamarsa ce ga bayinsa

6. Duk halittun Allah na sama da na ƙasa in ban da mutum da aljani, suna yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) sujjada, kowannensu gwargwadon yadda ya hore masa tasa sujjadar. Mutane da aljannu ne kawai ake samun wasu suna bijire wa bautar Allah shi kaɗai, sai sun haɗa shi da wasu.

7. Matsayin adalci a Musulunci babba ne, shi ya sa Allah ya yi umarni da tsayar da shi tun daga farkon yin halitta a bayan ƙasa.

8. Wajibi ne ga mutane da aljannu su tabbatar da cewa, duk wata ni’ima da suke gani a bayan ƙasa daga Allah ne, kuma su yi masa godiya a kanta. Bai dace su ƙaryata ta ko su butulce masa game da ita ba.

55-Suratur Rahman

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Hadisai da dama sun nuna ana kiran ta da '*Suratur Rahman*'. [Dubi, Abu Dawud #1396 da Tirmizi #329]. An kuma kira ta ne da wannan suna saboda da lafazin "*Ar-Rahman*" aka buɗe ta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin yawancin malamai da sahabbai da tabi'ai. Amma an sami wata ruwaya daga Abdullahi ɗan Abbas yana cewa Sura ce *Madaniyya*. [Dubi, *Mausu'atut Tafsiril Ma'athur*, Juzu'i na 21 shafi na 71].

3. Adadin Ayoyinta:
A lissafin malaman Sham da Kufa ayoyinta saba'in da takwas ne (78), a wurin malaman Madina da Makka kuwa adadinsu saba'in da bakwai ne (77), a wurin mutanen Basra saba'in da shida (76).

4. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba'in da uku (43), ta kuma sauka bayan '*Suratul Furkan*' kafin '*Suratu Faɗir*'.

5. Babban Jigonta:
Bayanin manya-manyan ni'imomin Allah da rahamarsa a duniya da lahira, domin kwaɗaitarwa ga yin imani da tsoratarwa game da kafirci.

19. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin mafi girman ni'imar Allah ga bayinsa, watau saukar da Alƙur'ani.
• Bayanin girman Kudurar Allah wajen kyautata halittar abubuwa masu ƙunshe da ni'imomi daban-daban ga ɗan'adam.
• Bayanin halittar aljannu da tabbatar da sakamakonsu a ranar alƙiyama.
• Tabbatar da cewa, komai mai ƙarewa ne in ban da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) tare da tunatar da mutane ranar alƙiyama wadda a cikinta ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai saka wa kowa a kan aikinsa.
• Yabo ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da yi masa kirari.

Suratur Rahman (1-13)
ٱلرَّحۡمَٰنُ ۝١ عَلَّمَ ٱلۡقُرۡءَانَ ۝٢ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ ۝٣ عَلَّمَهُ ٱلۡبَيَانَ ۝٤ ٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُ بِحُسۡبَانٖ ۝٥ وَٱلنَّجۡمُ وَٱلشَّجَرُ يَسۡجُدَانِ ۝٦ وَٱلسَّمَآءَ رَفَعَهَا
وَوَضَعَ ٱلۡمِيزَانَ ۝٧ أَلَّا تَطۡغَوۡاْ فِي ٱلۡمِيزَانِ ۝٨ وَأَقِيمُواْ ٱلۡوَزۡنَ بِٱلۡقِسۡطِ وَلَا تُخۡسِرُواْ ٱلۡمِيزَانَ ۝٩ وَٱلۡأَرۡضَ وَضَعَهَا لِلۡأَنَامِ ۝١٠ فِيهَا فَٰكِهَةٞ وَٱلنَّخۡلُ
ذَاتُ ٱلۡأَكۡمَامِ ۝١١ وَٱلۡحَبُّ ذُو ٱلۡعَصۡفِ وَٱلرَّيۡحَانُ ۝١٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ۝١٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. (Allah) Mai rahama.

2. Shi Ya koyar da Alƙur’ani.

3. Ya halicci mutum.

4. Ya koyar da shi bayani.

5. Rana da wata (suna tafiya) a tsare.

6. Tsirrai da bishiyoyi suna yin sujjada.

7. Sama kuma Ya ɗaga ta, Ya kuma kafa adalci.

8. Don kada ku yi zalunci a abin awo.

9. Kuma ku tabbatar da awo da adalci kada kuma ku tauye abin awo.

10. Kasa kuma Ya yi ta saboda talikai.

11. A cikinta akwai abin marmari da dabinai ma’abota kwasfa.

12. Da ƙwayoyi ma’abota ƙaiƙayi da kuma ganyaye masu ƙanshi.

13. To da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da ambaton sunansa 'Mai rahma' wanda yake nuna yalwatacciyar rahamarsa da ta game kowa da komai a nan duniya. Sannan ya bayyana cewa, shi ne ya koyar da karatun Alƙur’ani, ya sauƙaƙe haddarsa da fahimtar ma’anoninsa. Ya kuma kyautata halittar ɗan’adam, ya koyar da shi yadda zai yi bayanin abin da ke cikin zuciyarsa ta hanyar furuci ko rubutu.
Sai kuma ya bayyana cikar Kudurarsa da ɗa’ar halittu a gare shi da cewa, shi ne ya halicci rana da wata ya kuma tsara tafiyarsu a cikin sararin samaniya a kan wani lissafaffen tsari, domin mutane su riƙa sanin adadin shekaru da lissafin kwanakin wata.
Sannan ya bayyana cewa, tsirrai waɗanda ba sa tashi tsaye da bishiyoyi masu tsayawa a kan sandunansu, dukkansu suna yi masa sujjada suna miƙa wuya a gare shi.
Sai kuma ya bayyana cewa, shi ne ya halicci sama ya ɗaga ta domin ta zama kamar rufi ga halittunsa na ƙasa, ya kuma kafa adalci a bayan ƙasa ya kuma umarci bayinsa su tsayar da shi a tsakaninsu. Ya yi musu haka ne domin kada su yi zalunci su tsauye sikeli ko mudu, don haka ya jaddada musu cewa lalle su tsayar da sikeli a tsakaninsu da adalci, kada su kuskura su yi ƙwange wajen yin awo.
Sai kuma ya bayyana ni'imar da ya yi wa bayinsa da ya halicci ƙasa ya yi ta yadda ta dace da rayuwar halittunsa a kanta, ya kuma saka mata kayayyakin rayuwa iri-iri, kamar kayan marmari da dabinai masu kwasfa da ke ɗauke da ‘ya’yan dabinan da kuma ƙwayoyi masu ƙaiƙayi, kamar alkama da sha’iri da kuma ganyaye masu ƙanshi.
Bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gama lissafa waɗannan dangogin ni’ima da ya yi wa ɗan’adam da aljan a nan duniya sai ya tambaye su cewa, da wacce ni’ima ce daga cikin ni’imomin Ubangijinsu masu yawa suke ƙaryatawa?

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce : Manzon Allah (ﷺ) ya fita wajen sahabbansa, sai ya karanta musu '*Suratur Rahman*' daga farkonta har ƙarshenta, sai suka yi shiru suna sauraron sa, sai ya ce: "Me ya sa na ga kun yi shiru? Haƙiƙa na karanta wa aljannu wannan Surar a daren haɗuwata da su, sai ya zamanto sun fi ku iya bayar da amsa; duk sanda na karanta musu faɗar Allah: "To da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljanu) kuke ƙaryatawa ?" Sai su ce: 'Babu wani abu daga cikin ni'imominka da muke ƙaryatawa ya Ubangijinmu, yabo da godiya sun tabbata a gare ka'." [Tirmizi #3575].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin asalin halittar mutum na farko, watau Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da aljani na farko, watau Iblis. A cikin wannan bayani an ƙunshe ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan'adam na fifita shi a kan aljannu, don haka ne ma aka nemi mala'iku tare da Iblis su yi wa Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) sujjada.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi ta maimaita tunasar da mutane da aljannu game da ni'imomin da ya yi musu bayan ya ambaci kowace ni'ima. Yin hakan yana nuna kamalar Kudurarsa da yawan kyautayinsa ga bayinsa, da haka ne kuma ya cancanci a bauta masa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da wani abu wanda bai mallaki komai na ni'imtarwa ba.

3. Mahudar rana biyu da mafaɗarta biyu, ana nufin bambanci tsakanin mahudarta da mafaɗarta a lokacin sanyi da lokacin zafi, ko kuma lokacin damina da lokacin kaka.

4. Wajabcin godiya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a kan ni'imominsa ga mutane da aljannu.

Suratur Rahman (14-25)
خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِن صَلۡصَٰلٖ كَٱلۡفَخَّارِ ١٤ وَخَلَقَ ٱلۡجَآنَّ مِن مَّارِجٖ مِّن نَّارٖ ١٥ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ١٦ رَبُّ ٱلۡمَشۡرِقَيۡنِ وَرَبُّ ٱلۡمَغۡرِبَيۡنِ ١٧ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ١٨ مَرَجَ ٱلۡبَحۡرَيۡنِ يَلۡتَقِيَانِ ١٩ بَيۡنَهُمَا بَرۡزَخٞ لَّا يَبۡغِيَانِ ٢٠ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٢١ يَخۡرُجُ مِنۡهُمَا ٱللُّؤۡلُؤُ وَٱلۡمَرۡجَانُ ٢٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٢٣ وَلَهُ ٱلۡجَوَارِ ٱلۡمُنشَـَٔاتُ فِي ٱلۡبَحۡرِ كَٱلۡأَعۡلَٰمِ ٢٤ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٢٥

14. Ya halicci mutum daga busasshen taɓo kamar kasko.

15. Ya kuma halicci aljani daga harshen wuta.

16. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

17. Ubangijin mahudar rana biyu da mafaɗarta biyu.

18. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

19. Ya gudanar da koguna guda biyu suna haɗuwa (da juna).

20. A tsakaninsu (kuma) akwai wani shamaki da ya hana su shiga juna.

21. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

22. Lu’ulu’u da murjani suna fita daga cikinsu.

23. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

24. Jiragen ruwa kuma da aka yi su suna gudu a cikin kogi kamar manya-manyan duwatsu nasa ne.

25. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu alamomi na Kudurarsa da cikar ikonsa, inda ya bayyana cewa, ya halicci mutum, watau Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga busasshen taɓo mai amo kamar kasko, watau bayan taɓon ya bushe sai ya riƙa yin ƙara idan an ƙwanƙwasa shi, kamar ana ƙwanƙwasa kasko. Ya kuma halicci uban aljannu, watau Iblis daga tsantsar harshen wuta.

An karɓo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “An halicci mala’iku daga haske, an kuma halicci aljani daga wuta, an kuma halicci Adamu daga abin da aka siffanta muku.” [Muslim #2996 da Ahmad #12303].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi mutane da aljannu cewa, da wacce ni’imar ce daga cikin ni’imominsa masu yawa suke ƙaryatawa?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, shi ne Ubangijin mahudar rana biyu da mafaɗarta biyu, watau a lokacin sanyi da lokacin zafi, shi kaɗai ne mai gudanar da su, dukkansu kuma suna ƙarƙashin ikonsa ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cikar Kudurarsa dangane da koguna, yayin da ya gauraya ruwan koguna biyu, mai daɗi da mai zartsi, watau a ido ana ganin su suna haɗuwa da juna, amma a tsakaninsu akwai wani shamaki wanda yake hana su gauraya da juna, don haka mai daɗi zai ci gaba da kasancewa mai daɗi, mai zartsi shi ma zai ci gaba da zama mai zartsi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi mutane da aljannu cewa da waɗanne ni’imominsa ne suke ƙaryatawa?
Waɗannan koguna biyu kuma ana fitar da lu’ulu’u da murjani, watau ana nufin cewa suna fita daga cikin kogi mai zartsi wanda yake tare da mai daɗi wuri guda.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi kaɗai ne yake da ikon gudanar da manya-manyan jiragen ruwa a cikin kogi, suna tafiya kamar manyan duwatsu, mutane suna hawan su tare da kayayyakinsu masu nauyi su yi ta zirga-zirga da su ƙasa-ƙasa. Babu shakka wannan babbar ni’ima ce daga ni’imomin Allah masu yawa, don haka ya sake tambayar mutane da aljannu cewa da wacce ni’imar ce suke ƙaryatawa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani abu da yake a bayan ƙasa mai gushewa ne ya ƙare babu makawa. Babu mai wanzuwa sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffantu da siffar girma da karamci. Shi ne kuma mai yalwar karamci da kyauta ga bayinsa, yana karrama waliyyansa da dangogin karramawa iri-iri, su kuma suna matuƙar son sa suna girmama shi suna bauta masa shi kaɗai.

3. Tsananin buƙatuwar halittun Allah na sama da na ƙasa zuwa gare shi domin cikar wadatarsa da kyautarsa, kowane lokaci Allah yana cikin wasu harkoki na al’amuran bayinsa, yana wadata wasu, ya talauta wasu, ya ba wasu lafiya, ya jarrabi wasu da cututtuka, ya ɗaga darajar wasu, ya ƙasƙanta wasu, yana rayawa yana kashewa; wani al’amari ba ya shagaltar da shi daga wani; yawan roƙon masu roƙo ba ya fusata shi; ba ya rikicewa don yawan masu roƙon sa. Tsarki ya tabbata ga Allah mai kowa mai komai.

4. Dukkan al’amuran Ubangiji hukunce-hukuncensa ne waɗanda ya riga ya ƙaddara su tun fil azal, su ne yake zartarwa a kan bayinsa, a lokutan da suka dace da hikimarsa da masalahar bayinsa. Waɗannan al’amura kuwa sun ƙunshi al’amuran addini, watau umarninsa da haninsa; sun kuma ƙunshi al’amuran rayuwa waɗanda yake gudanarwa a kan bayinsa a rayuwarsu ta duniya har lokacin da ajalin zamansu a nan duniya zai ƙare, daga nan kuma sai ya zartar musu sakamakonsu, ya nuna musu adalcinsa da falalarsa da yawan ihsaninsa a gare su.

Suratur Rahman (26-30)

كُلُّ مَنْ عَلَيْهَا فَانٍ ﴿٢٦﴾ وَيَبْقَىٰ وَجْهُ رَبِّكَ ذُو ٱلْجَلَٰلِ وَٱلْإِكْرَامِ ﴿٢٧﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٢٨﴾ يَسْـَٔلُهُۥ مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ كُلَّ يَوْمٍ هُوَ فِى شَأْنٍ ﴿٢٩﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٣٠﴾

26. Dukkan wanda yake kanta (ƙasar) ƙararre ne.

27. Fuskar Ubangijinka kuwa Ma’abocin girma da karamci ne kawai take wanzuwa.

28. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

29. Duk wanda yake cikin sammai da ƙasa yana roƙon Sa. Kowane lokacin Shi a cikin wani sha’ani yake.

30. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa mutum da aljani cewa, su sani duk wani abu da yake bayan ƙasa, na mutane da aljannu da dabbobi da sauran halittu na ruwa da na tudu, dukansu masu ƙarewa ne, su gushe kamar ba a yi su ba, babu wanda zai wanzu sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) Ma’abocin girma da karamci ga bayinsa, shi kam yana nan har abada, gushewa ba za ta riske shi ba balle ƙarewa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tambayar mutane da aljannu cewa, da waɗanne ni’imomin Ubangijinsu ne suke ƙaryatawa?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin buƙatuwar halittunsa na sama da na ƙasa gare shi, domin cikar wadatarsa da kyautayinsu. Mala’iku a cikin sammai da mutane da aljannu a ƙasa dukkansu suna roƙon sa ya biya musu buƙatunsu babu ƙaƙƙautawa. Shi kuwa a kowane lokaci yana cikin wani al’amari da ya shafi al’amuran bayinsa, wanda ya danganci rayawa da kashewa da arzutawa da talautawa da sauransu.
Sai kuma ya maimaita tambayarsa ga mutane da aljannu game da ni’imomin Ubangijinsu da suke ƙaryatawa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da hisabi ga mutane da aljannu a ranar alƙiyama.

2. Abin da zai faru ga mutane da aljannu masu miyagun laifuffuka a ranar alƙiyama na ƙalubalantar su da su fice daga sasannin sammai da ƙasa idan za su iya tsere wa Allah ko su fi ƙarfin Kudurarsa, domin ba za su iya samun yin haka ba sai idan suna da wata ƙudura da ta fi ta Allah ko wani iko da ya zarce nasa, wanda kuwa sun tabbatar ba su da shi.

3. Kafirai za su gamu da azaba iri-iri a ranar lahira.

4. Tsoratarwa ma wata ni’ima ce daga ni'imomin Allah, domin takan sanya bawa ya shiga taitayinsa ya dawo kan hanya madaidaiciya, domin guje wa mummunan sakamako.

Suratur Rahman (31-36)
سَنَفۡرُغُ لَكُمۡ أَيُّهَ ٱلثَّقَلَانِ ٣١ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٣٢ يَٰمَعۡشَرَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِ إِنِ ٱسۡتَطَعۡتُمۡ أَن تَنفُذُواْ مِنۡ أَقۡطَارِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ فَٱنفُذُواْۚ لَا تَنفُذُونَ إِلَّا بِسُلۡطَٰنٍ ٣٣ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٣٤ يُرۡسَلُ عَلَيۡكُمَا شُوَاظٞ مِّن نَّارٖ وَنُحَاسٞ فَلَا تَنتَصِرَانِ ٣٥ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٣٦

31. Ba da daɗewa ba za Mu dawo kanku ya ku mutane da aljannu.

32. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

33. Ya ku jama’ar aljannu da mutane, idan kun sami ikon ficewa daga cikin sassan sammai da ƙasa to ku fice. Ba za ku fice ba sai da samun wani ƙarfi.

34. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

35. Za a aiko muku (ku mutane da aljannu) da balbalin wuta da kuma hayaƙi, saboda haka ba za ku iya kare kanku (daga gare shi) ba.

36. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da bayinsa mutane da aljannu da cewa, ba da jimawa ba zai dawo kansu, watau a ranar alƙiyama domin yi musu hisabi a kan ayyukansu kyawawa da munana, zai kuma saka wa kowa gwargwadon aikinsa. Don haka ya sake jan hankalinsu game da ƙaryata wata ni’ima daga cikin ni’imominsa gare su.
Sannan ya sanar da su cewa, a ranar alƙiyama idan ya tattara mutane da aljannu zai umarce su da cewa, idan har suna da iko kuma sun isa to su fice daga sassan sammai da na ƙasa, su guje wa damƙarsa. Ya tabbatar musu da cewa, tabbas ba za su iya samun wata mafita ba da za su kuɓuce wa Allah sai idan suna da wata hujja ko wani ƙarfi, wanda kuwa su ma sun tabbata ba su da shi.
Sai ya sake jan kunnensu game da ƙaryata wata ni’ima daga cikin ni’imominsa gare su.
Sai kuma ya bayyana musu abin da zai faru da su a wannan rana ta alƙiyama inda zai aiko musu da balbalin wuta marar hayaƙi da kuma hayaƙi marar balbali, saboda haka ba za su iya kare kansu daga gare shi ba, ba kuma za su iya taimaka wa junansu ba.
To wannan tsoratarwar da yake yi musu ita kanta wata ni’ima ce a gare su, don haka ya sake jan kunnensu ta hanyar tambayar su game da ni’imarsa da suke ƙaryatawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da wargajewar tsarin sama yayin da alƙiyama ta zo, lokacin da sama za ta tsattsage mala'iku su yi ta saukowa daga cikinta.

2. A ranar alƙiyama akwai wuraren yada zango daban-daban; akwai inda za a yi wa mutane tambaya; akwai kuma inda ba za a tambaye su ba, ba ma za a ba su damar yin magana ba.

3. A ranar alƙiyama Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai bambance tsakanin muminai da kafirai da wasu alamomi masu rarrabe kowane ɓangare daga cikinsu.

4. Za a yi wa kafirai mummunar damƙa a lahira yayin jefa su cikin wutar Jahannama, babu kuma wanda zai iya kuɓucewa ya gudu.

5. Yayin da zafin wutar Jahannama ya tsananta ga kafirai za su nemi abin da za su sanyaya jikinsu da shi, sai su hango wani ruwa sai su nufi inda yake sai kuma tsananin zafinsa ya sake koro su sai su koma cikin wutar. Hakanan za su yi ta kai-kawo tsakanin wutar Jahannama da wannan tafasasshen ruwa.

Suratur Rahman (37-45)
فَإِذَا ٱنشَقَّتِ ٱلسَّمَآءُ فَكَانَتۡ وَرۡدَةٗ كَٱلدِّهَانِ ٣٧ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٣٨ فَيَوۡمَئِذٖ لَّا يُسۡـَٔلُ عَن ذَنۢبِهِۦٓ إِنسٞ وَلَا جَآنّٞ ٣٩ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٠ يُعۡرَفُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ بِسِيمَٰهُمۡ فَيُؤۡخَذُ بِٱلنَّوَٰصِي وَٱلۡأَقۡدَامِ ٤١ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٢ هَٰذِهِۦ جَهَنَّمُ ٱلَّتِي يُكَذِّبُ بِهَا ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٤٣ يَطُوفُونَ بَيۡنَهَا وَبَيۡنَ حَمِيمٍ ءَانٖ ٤٤ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٥

37. Sannan idan sama ta kekkece ta zama jajir kamar jar fata.

38. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

39. Sannan a wannan rana ba a tambayar mutum ko aljan laifinsa.

40. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

41. Ana gane manyan masu laifi da alamominsu, sai a kama su ta makwarkwaɗa da dugadugai.

42. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

43. (Za a ce da su): Wannan ita ce Jahannamar da manyan masu laifi suke ƙaryatawa.

44. Za su riƙa kai-kawo tsakaninta da tafasasshen ruwa mai tsananin zafi.

45. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda a ranar alƙiyama sama za ta tsattsage ta zama ja kamar jan fure ko jar fata, saboda an gusar da hasken taurarinta gaba ɗaya, domin wani babban sauyi da Allah ya samar a sammai da ƙasa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya maimaita tambayar ga mutane da aljannu cewa da waɗanne ni'imomin Ubangijinsu ne suke ƙaryatawa?

Sai ya ci gaba da bayanin cewa, a wannan ranar ta alƙiyama ba za a tsaya tambayar wani mutum ko aljani game da laifin da ya aikata ba, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya san komai na ayyukansa ba ya kokwanto a kan abin da kowa ya aikata, domin kuwa duk wasu masu miyagun laifuka za a gane su da alamominsu, saboda fuskokinsu za su yi baƙi ƙirin, idanuwansu kuma za su zama jajaye jawur, daga nan sai a damƙe su ta makwarkwaɗarsu tare da dugadugansu a watsa su cikin wutar Jahannama.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tambayar mutane da aljannu cewa da waɗanne ni'imomin Ubangijinsu ne suke ƙaryatawa?
Sannan bayan mala'iku sun jefa kafirai cikin wutar Jahannama sai su riƙa faɗa musu cewa, wannan fa ita ce Jahannamar da suke ƙarayatawa a duniya, ga su nan yau a cikinta tsundum babu sauran maganar ƙaryatawa kuma, domin kuwa a cikinta ne za su yi ta kai-kawo tsakaninta da tafasasshen ruwa mai tsananin zafi. To da waɗanne ni'imomin Ubangijinsu ne suke ƙaryatawa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin jin tsoron Allah da halarto da tsayuwa a gabansa a ranar alƙiyama.

2. Bayanin ɗimbin ni'imomin gidan Aljanna.

3. Yabon kamun kan 'yan matan gidan Aljanna yana nuna falalar kamun kai ga 'ya mace da kasancewarta mafi kyan kwalliya da za ta nuna wa ɗa namiji.

4. Irin aikin mutum irin sakamakon da zai gani.

Suratur Rahman (46-61)
وَلِمَنۡ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ جَنَّتَانِ ٤٦ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٧ ذَوَاتَآ أَفۡنَانٖ ٤٨ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٩ فِيهِمَا عَيۡنَانِ تَجۡرِيَانِ ٥٠
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٥١ فِيهِمَا مِن كُلِّ فَٰكِهَةٖ زَوۡجَانِ ٥٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٥٣ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ فُرُشِۭ بَطَآئِنُهَا مِنۡ إِسۡتَبۡرَقٖۚ
وَجَنَى ٱلۡجَنَّتَيۡنِ دَانٖ ٥٤ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٥٥ فِيهِنَّ قَٰصِرَٰتُ ٱلطَّرۡفِ لَمۡ يَطۡمِثۡهُنَّ إِنسٞ قَبۡلَهُمۡ وَلَا جَآنّٞ ٥٦ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ٥٧ كَأَنَّهُنَّ ٱلۡيَاقُوتُ وَٱلۡمَرۡجَانُ ٥٨ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٥٩ هَلۡ جَزَآءُ ٱلۡإِحۡسَٰنِ إِلَّا ٱلۡإِحۡسَٰنُ ٦٠ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ٦١

46. Duk wanda kuwa ya ji tsoron tsayuwa (gaban) Ubangijinsa yana da Aljanna biyu.

47. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

48. Ma'abota rassan bishiyoyi.

49. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

50. A cikinsu akwai idanuwa (na ruwa) guda biyu masu gudana.

51. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

52. A cikinsu akwai (dangi) biyu na kowane abin marmari.

53. Da waɗanne ni'imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

54. Suna kishingiɗe a kan shimfiɗu da shafin cikinsu na kakkauran alhariri ne. Kuma ‘ya’yan bishiyoyin Aljannatai biyun kusa suke (da kowa).

55. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

56. A cikinsu akwai (mata) masu taƙaita kallo (ga mazajensu, waɗanda) wani mutum ko aljan bai taɓa shafar su ba a gabaninsu.

57. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

58. Kai ka ce su yaƙutu ne da murjani.

59. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

60. Shin akwai wani sakamako na kyautatawa in ba kyautatawa ba?

61. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu ni’imomin Aljanna da zai saka wa muminai masu tsoron sa da su, inda ya ce, duk wani muminin da ya ji tsoron tsayawa gaban Ubangijinsa a ranar alƙiyama ya kuma yi aiki nagari, to yana da aljannatai guda biyu waɗanda ya bayyana siffofinsu har guda shida:
Na ɗaya, suna da rassan bishiyoyi masu yawa da girma da inuwoyi luf-luf.
Na biyu, a cikinsu kuma akwai idanuwan ruwa masu gudana ko’ina suna shayar da bishiyoyi da shuke-shuken cikinsu.
Na uku, kowane nau’i na kayan marmari a cikinsu ana kawo musu bibbiyu ne, watau ɗanye da busasshe, kowanne cikinsu yana da launinsa da ɗanɗanonsa na daban, fari da ja da mai zaƙi da mai tsami.
Na huɗu, akwai shimfiɗu na alfarma da ‘yan Aljannar za su riƙa kishingiɗa a kansu, ƙasansu na alhariri ne mai kauri mai ban sha’awa, ballanta kuma samansu inda suke kwanciya a kai ko zama, abin sai dai wanda ya gani kawai.
Na biyar, ‘ya’yan itatuwan waɗannan aljannatai biyu kusa-kusa suke ta yadda ɗan Aljanna ko yana kishingiɗe zai iya miƙa hannunsa ya tsinko.
Na shida, a cikinsu kuma akwai matan Hurul-Ini waɗanda ba sa kallon kowa sai mazajensu, waɗanda kuma babu wani mahaluƙi mutum ko aljani da ya taɓa taɓa su sai mazajensu. Allah ya yi musu tsalelen kyau da haske, idan ka gan su sai ka ga suna haske da sheƙi kamar yaƙutu da murjani.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah ya ce: “Farkon ayarin da za su shiga Aljanna za su shige ta ne suna masu haske kamar wata daren goma sha huɗu, waɗanda za su biyo bayansu kuwa suna haske kamar tauraron da ya fi kowanne tauraro haske. Zukatansu kamar zuciyar mutum ɗaya, babu saɓani ko ƙyamar juna a tsakaninsu. Duk mutum ɗaya daga cikinsu yana da mata biyu, kowace ɗaya daga cikinsu ana gano ɓargon ƙwaurinta ta bayan tsokar nama saboda tsananin kyau. Suna yi wa Allah tasbihi suna tsarkake shi safe da yamma. Ba sa rashin lafiya ba sa face majina ko tofar da yawu. Kwanukansu na zinariya ne da azurfa, matajan kansu kuwa na zinariya ne, makamashin turaren wutarsu shi ne *Al-ud*, guminsu kuwa ƙamshin almiski yake.” [Bukhari #2346 da Muslim #2834].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, babu wani sakamako ga duk wanda ya kyautata biyayya gare shi sai dai kyakkyawan sakamako da zai samu daga Ubangijinsa.

To yanzu da waɗannen ni’imomin Ubangiji ne mutane da aljannu suke ƙaryatawa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan aljannatan biyu ƙasa suke da na farko. Idan aka duba siffofinsu za a iya fahimtar cewa an fifita na farko a kansu ta fuskoki goma, kamar haka:
Na farko, ya siffanta aljannatai biyu na farko da cewa ma’abota rassan bishiyoyi ne, amma bai siffanta aljannatai na biyu da wannan ba.
Na biyu, ya siffanta idanuwan ruwa a na farko da cewa ‘masu gudana’, amma na biyu sai ya ce ‘masu feshi’. A fili yake cewa ‘mai gudana’ ya fi ‘mai feshi’, domin shi mai gudana zai iya haɗa feshi da gudana saɓanin mai feshi kaɗai.
Na uku, a na farko ya ce: “A cikinsu akwai dangi biyu na kowane abin marmari.” Amma a na biyu sai ya ce: “A cikinsu akwai abin marmari da dabino da rumman.” Babu shakka siffar na farko ta fi nuna cika da kamala.
Na huɗu, ya bayyana shimfiɗun na farko da cewa bayansu na alhariri ne mai kauri, amma a na biyu sai kawai ya ambaci matasan kai masu korayen riguna da shimfiɗu masu kyau. A fili yake siffar shimfiɗun aljannatai biyu na farko sun fi na biyu cika da kyau.
Na biyar, ya bayyana kayan marmarin aljannatai biyu na farko da cewa kusa-kusa suke, amma bai faɗi haka game da na biyu ba.
Na shida, ya siffanta matan na farko da cewa masu taƙaita kallonsu ne ga mazajensu kaɗai. Wannan ya nuna cikar soyayyarsu ga mazajensu da amincewarsu da su har ma ba sa tunanin kallon wasu mazajen daban ba nasu ba. Amma a matan aljannatai na biyu sai ya siffanta su da cewa ‘suna kawwame a cikin tantuna’. Lalle matar da ta taƙaita kallonta a kan mijinta ta fi wadda sai da aka kawwame ta.
Na bakwai, ya siffanta matan aljannatai biyu na farko da cewa: “Kai ka ce su yaƙutu ne da murjani”, watau saboda tsananin kyansu da hasken fatarsu. Amma bai siffanta na biyu da haka ba.
Na takwas, a game da aljannatai biyu na farko ya rufe da cewa: “Babu wani sakamako na kyautatawa sai kyautatawa”. Wannan ya nuna cewa masu wannan sakamako su ne ma’abota kyautatawa cikakkiya, watau matakin ihsani wajen bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) don haka sakamakonsu ya fi cika.
Na tara, ya fara da siffanta aljannatai na farko ya kuma sanya su sakamako ne na wanda ya ji tsoron tsayuwa gabansa ranar alƙiyama. Wannan ya nuna shi ne mafi ƙololuwar sakamakon mai jin tsoron tsayuwa a gaban Ubangijinsa. To kasancewa masu tsoron tsayuwa gaban Allah ranar alƙiyama kashi biyu ne, akwai makusanta, watau *muƙarrabuna*; akwai kuma ma’abota dama, sai ya ambaci aljannatai biyu na *muƙarrabuna* da kuma biyu na ma’abota dama.
Na goma, shi kansa Allah cewa ya yi: “A ƙasa da su akwai wasu aljannatai guda biyu” wannan ƙarara ya nuna na farko su ne sama kuma su ne gaba. [Dubi, Ibnul Kayyim, *Hadil Arwah*, shafi na 102-104].

2. Tabbatar da kasuwar ‘yan Aljanna zuwa darajoji mabambanta gwargwadon kyawawan ayyukansu.

Suratur Rahman (62-78)

وَمِن دُونِهِمَا جَنَّتَانِ ﴿٦٢﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٦٣﴾ مُدْهَآمَّتَانِ ﴿٦٤﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٦٥﴾ فِيهِمَا عَيْنَانِ نَضَّاخَتَانِ ﴿٦٦﴾ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٦٧﴾ فِيهِمَا فَٰكِهَةٌ وَنَخْلٌ وَرُمَّانٌ ﴿٦٨﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٦٩﴾ فِيهِنَّ خَيْرَٰتٌ حِسَانٌ ﴿٧٠﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ﴿٧١﴾ حُورٌ مَّقْصُورَٰتٌ فِى ٱلْخِيَامِ ﴿٧٢﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٧٣﴾ لَمْ يَطْمِثْهُنَّ إِنسٌ قَبْلَهُمْ وَلَا جَآنٌّ ﴿٧٤﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ﴿٧٥﴾ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ رَفْرَفٍ خُضْرٍ وَعَبْقَرِىٍّ حِسَانٍ ﴿٧٦﴾ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ﴿٧٧﴾ تَبَارَكَ ٱسْمُ رَبِّكَ ذِى ٱلْجَلَٰلِ وَٱلْإِكْرَامِ ﴿٧٨﴾

62. A ƙasa da su kuma akwai wasu aljannatai guda biyu.

63. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

64. Masu tsananin ƙore.

65. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

66. A cikinsu (kuma) akwai idanuwan (ruwa) guda biyu masu feshi.

67. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

68. A cikinsu (kuma) akwai abin marmari da dabino da ruman.

69. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

70. A cikinsu (watau gidajen Aljannar) akwai mata nagartattu kyawawa.

71. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

72. (Matayen) masu fari da baƙin ido ne, suna kawwame cikin tantuna.

73. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

74. Wani mutum ko aljan bai taɓa shafar su ba a gabaninsu.

75. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

76. Suna kishingiɗe a kan matasan kai koraye, da kuma kilisai kyawawa.

77. Da waɗanne ni’imomin Ubangijinku ne (ku mutane da aljannu) kuke ƙaryatawa?

78. Albarkatun sunan Ubangijinka Ma’abocin girma da ɗaukaka sun yawaita.

A waɗannan ayoyi kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, akwai wasu aljannatai biyu ƙasa da waɗanda aka ambata da farko waɗanda su ma ya siffanta su da siffofi biyar, su ne:
Na ɗaya, bishiyoyinsu da shuke-shukensu koraye ne shar masu matuƙar ban sha’awa.
Na biyu, a cikinsu akwai wasu idanuwan ruwa biyu masu feshin ruwa da ƙarfi ba ƙaƙƙautawa.
Na uku, a cikinsu akwai kayan marmari masu yawa da itatuwan dabino manya-manya da kuma rumman, waɗanda koyaushe ake samu ba sa yankewa.
Na huɗu, a cikinsu har ila yau akwai mata masu kyawawan halaye masu kyan sura da fari da baƙin ido, kawwamammu a cikin tantuna, babu mai ganin su su ma ba sa ganin kowa sai mazajensu, don haka ne ma babu wani mahaluƙi mutum ko aljani da ya taɓa kusantar su kafin mazajensu.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash’ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Tantin (‘yan Aljanna) wani kewayayyen lu’ulu’u ne, tsawonsa a sama mil talatin ne. A cikin kowane rukunin tantin mumini yana da iyali da sauran ba sa ganin su.” [Bukhari #3243 da Muslim #2838].
Na biyar, a cikinsu akwai matasan kai waɗanda aka naɗe su cikin korayen riguna da kuma shimfiɗu masu tsananin kyau, a kansu ne ‘yan Aljanna suke kishingiɗa suna morewa.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Akwai wasu aljannatai biyu na azurfa, kwanukansu da duk wani abu da yake cikinsu na azurfa ne. Da kuma wasu aljannatai biyu na zinari, duk wani abin da yake cikinsu shi ma na zinari ne. Babu wani abu da ya zama shamaki tsakaninsu da ganin Ubangijinsu sai gwadon ƙasaita da ke kan fuskarsa, suna cikin Aljannar dawwama." [Bukhari #4878 da Muslim #180].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nanata tambayarsa ga mutane da aljannu cewa da waɗanne ni'imominsa ne suke ƙaryatawa?Allah kuma a ƙarshen Surar ya yabi kansa da cewa albarkatun sunansa sun yawaita ya kuma girmama, shi ne ma'abocin girma da karamci ga bayinsa.

An karɓo daga Rabi'a ɗan Amir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku lizimci faɗar: "*Ya Zal-Jalali Wal Ikram*". [Ahmad #17596 da Hakim #1836].

An karɓo daga Sauban (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance da zarar ya gama salla sai ya ce: "*Allahumma Antas Salamu Wa Minkas Salamu Tabarakta Ya Zal Jalali Wal Ikram*." [Muslim #591]

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da aukuwar ranar alƙiyama yayin da lokacinta ya zo, kuma a ranar kafirai masu ƙaryata zuwanta za su saduda su miƙa wuya, su yarda da gaskiyar da aka yi ta gaya musu a duniya suna ƙaryatawa, amma a lokacin sun riga sun makaro.

2. Ranar alƙiyama ita ce haƙiƙanin ranar da kowa zai gane matsayinsa, wasu da ake ganin su masu ɗaukaka a duniya su ƙasƙanta a ranar, wasu kuma da ake yi wa kallon ƙasƙantattu a duniya ta bayyana su ne maɗaukaka.

3. A lokacin zuwan ranar alƙiyama duk tsarin ginin duniya, sama da ƙasa, zai rugurguje don a tabbatar da sake buɗe wani kundin rayuwa sabo.

4. Kashe-kashen mutane a lahira, da matsayin kowa a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

56-Suratul Waƙi’a

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunanta ‘*Suratul Waƙi’a,*’ kamar yadda yake a littattafan tafsiri da hadisi da *masahifu*.
An kuma kira ta ne da wannan suna saboda lafazin ‘*Al-Waƙi’a*’ da ya zo a ayarta ta 1. Yana kuma nufin ranar alƙiyama.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Duk malamai sun haɗu a kan cewa Sura ce *Makkiyya* gaba ɗayanta. An samu wasu malamai masu togace wasu ayoyi da cewa sun sauka a Madina a halin tafiya, amma ra’ayi ne mai rauni sosai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba’in da shida (46) a jerin saukar surorin Alƙur’ani. Ta sauka bayan ‘*Suratu Ɗaha*’ kafin ‘*Suratus Shu’ara’i*’.

4. Adadin ayoyinta:
Ayoyinta tis’in da shida ne (96) a lissafin mutanen Kufa. A wurin malaman Basra kuwa su tis’in da bakwai ne (97), a lissafin mutanen Madina da Makka da Sham adadinsu tis’in da tara (99) ne.

5. Babban Jigonta:
Ta ƙunshi tsoratarwa game da ranar alƙiyama da kuma aukuwarta babu makawa da kashe-kashen mutane a cikinta da bayanin sakamakon kowane kaso.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tunatarwa game da ranar alƙiyama da tabbatar da aukuwarta.
• Bayani a kan abin da zai faru a bayan ƙasa lokacin zuwan alƙiyama.
• Bayani game da ‘yan Aljanna da wasu ni’imominta.
• Bayani game da ‘yan wuta da azabar da za su gamu da ita saboda sun ƙaryata ranar alƙiyama.
• Tabbatar da tashin matattu da tattara su domin yi musu hisabi da sakamako.
• Kafa ƙwararan hujjoji na la’akari da abubuwan da Allah ya samar waɗanda babu su a da, masu nuna lalle Allah zai iya sake tashin matattu.
• Kafa hujja da zare ran mai mutuwa daga jikinsa a gaban makusantansa babu mai iya hanawa ko dawo da shi bayan ya fita, don haka duk wanda ya yi wannan aiki lalle zai iya dawo da ran matacce.
• Tabbatar da cewa Alƙur’ani saukakke ne daga Allah, kuma ni’ima ce ga mutane da ya wajaba su yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) godiya a kanta.

Suratul Waƙi’a (1-12)

إِذَا وَقَعَتِ ٱلۡوَاقِعَةُ ۝١ لَيۡسَ لِوَقۡعَتِهَا كَاذِبَةٌ ۝٢ خَافِضَةٞ رَّافِعَةٌ ۝٣ إِذَا رُجَّتِ ٱلۡأَرۡضُ رَجّٗا ۝٤ وَبُسَّتِ ٱلۡجِبَالُ بَسّٗا ۝٥ فَكَانَتۡ هَبَآءٗ مُّنۢبَثّٗا ۝٦ وَكُنتُمۡ أَزۡوَٰجٗا ثَلَٰثَةٗ ۝٧ فَأَصۡحَٰبُ ٱلۡمَيۡمَنَةِ مَآ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَيۡمَنَةِ ۝٨ وَأَصۡحَٰبُ ٱلۡمَشۡـَٔمَةِ مَآ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَشۡـَٔمَةِ ۝٩ وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلسَّٰبِقُونَ ۝١٠ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلۡمُقَرَّبُونَ ۝١١ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ۝١٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Idan mai afkowa ta afku (watau alƙiyama).

2. Babu wani (rai) mai ƙaryata aukuwarta.

3. Mai ƙasƙantarwa ce mai ɗaukakawa.

4. Idan aka girgiza ƙasa girgizawa.

5. Aka kuma dandaƙe duwatsu dandaƙewa.

6. Suka zama ƙura abar sheƙewa.

7. Kuka kuma kasance dangogi guda uku.

8. To ma’abota dama fa, mamakin darajar ma’abota dama!

9. Da kuma ma’abota hagu, mamakin wulaƙantar ma’abota hagu!

10. Da kuma masu rige-rige (zuwa alheri).

11. Waɗannan su ne makusanta.

12. A cikin gidajen Aljanna na ni’ima.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tabbatar da aukuwar tashin alƙiyama idan lokacinta ya yi, kuma idan ta auku babu wani rai da zai iya ƙaryata ta, kamar yadda yake faruwa a nan gidan duniya, inda wasu kafirai suke cewa ƙarya ne babu ita.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta ranar alƙiyama da cewa rana ce da za ta ƙasƙantar da kafirai, domin kuwa za a jefa su cikin wuta kowa yana gani, ta kuma ɗaga likkafar muminai masu tsoron Allah, yayin da za a shigar da su gidajen Aljanna kowa yana gani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin aukuwar ranar alƙiyama ƙasa za ta yi wata babbar girgiza da ba ta taba yin irinta ba, za kuma a yi fata-fata da duwarwatsu su zama kamar ƙura abar sheƙewa, watau ƙasa ta dawo fili fetal babu tudu ko kwari, kuma babu komai a kanta. A ranar mutane za su kasu gida uku:
Na farko, ma’abota hannun dama, waɗanda za su karɓi littattafan ayyukansu da hannayensu na dama. Waɗannan suna da babban matsayi.
Na biyu, ma’abota hannun hagu, watau waɗanda za su karɓi littattafansu na ayyuka a hannayensu na hagu. Waɗannan kam matsayinsu ya munana ainun.

Na uku, masu rige-rige wajen ayyukan alheri a duniya, to waɗannan su ne za su riga kowa shiga Aljanna a lahira, kuma su ne makusantan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) waɗanda zai sanya su a cikin gidajen Aljanna na ni'ima, su yi rayuwar jin daɗi a cikinsu babu yankewa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Mutanen da suka tsere fintinkau cikin aikin Allah suna da yawa a cikin mabiya annabawan da suka gabata. Idan aka tattara su gaba ɗaya yawansu zai fi na waɗanda suke cikin wannan al'umma. Wannan kuma ba ya nuna fifikonsu a kan wannan al'umma domin yawansu tare da kowane annabi da ya gabata bai kai yawansu a cikin wannan al'umma ba, sun yi yawa ne idan an haɗa su gaba ɗayansu a tare.
Wasu daga cikin malamai, kamar Al-Hasanul Basri da Muhammadu ɗan Sirin, suna ganin gaba ɗaya ayar tana magana ne a kan wannan al'ummar ta Manzon Allah (ﷺ), don haka tana nufin waɗannan bayin Allah masu rige-rige wajen biyayya ga Allah sun fi yawa a cikin al'ummar farko, watau magabatan wannan al'umma, amma 'yan kaɗan ne a cikin na ƙarshenta. Wannan shi yake nuna fifikon wannan al'umma a kan sauran al'ummun da suka gabata.
Wasu malamai kuma kamar Ibni Kasir suna ganin ayar tana iya haɗe duk al'ummu gaba ɗaya, amma tana nufin a cikin kowace al'umma an fi samun waɗannan bayin Allah da yawa a farkonta, a sami kaɗan a ƙarshenta. Amma abin da shi Ibn Kasir ya fi rinjayarwa shi ne cewa ayar gaba ɗaya tana nufin wannan al'umma.

2. Ayyuka nagari su ne sanadiyyar shiga gidan Aljanna.

Suratul Waƙi'a (13-26)
ثُلَّةٌ مِّنَ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٣ وَقَلِيلٞ مِّنَ ٱلۡأٓخِرِينَ ١٤ عَلَىٰ سُرُرٖ مَّوۡضُونَةٖ ١٥ مُّتَّكِـِٔينَ عَلَيۡهَا مُتَقَٰبِلِينَ ١٦ يَطُوفُ عَلَيۡهِمۡ وِلۡدَٰنٞ مُّخَلَّدُونَ ١٧ بِأَكۡوَابٖ
وَأَبَارِيقَ وَكَأۡسٖ مِّن مَّعِينٖ ١٨ لَّا يُصَدَّعُونَ عَنۡهَا وَلَا يُنزِفُونَ ١٩ وَفَٰكِهَةٖ مِّمَّا يَتَخَيَّرُونَ ٢٠ وَلَحۡمِ طَيۡرٖ مِّمَّا يَشۡتَهُونَ ٢١ وَحُورٌ عِينٞ ٢٢ كَأَمۡثَٰلِ
ٱللُّؤۡلُوِ ٱلۡمَكۡنُونِ ٢٣ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٢٤ لَا يَسۡمَعُونَ فِيهَا لَغۡوٗا وَلَا تَأۡثِيمًا ٢٥ إِلَّا قِيلٗا سَلَٰمٗا سَلَٰمٗا ٢٦

13. Su jama'a ne (masu yawa) daga (al'ummun) farko.

14. Kuma kaɗan ne daga (al'ummun) ƙarshe.

15. Suna kan gadaje masu adon zinari.

16. Suna kishingiɗe a kansu suna fuskantar juna.

17. Yara samari dawwamammu (masu hidima) za su riƙa zagaya su.

18. Da kofuna (marasa mariƙai) da butoci masu hannaye da kuma ƙokuna na giya.

19. Ba sa ciwon kai saboda ita, kuma ba sa buguwa.

20. Da kuma ababan marmari na abin da suke so su zaɓa.

21. Da kuma naman tsuntsaye na abin da suke sha'awa.

22. Da kuma matan Hurul-Ini.

23. Kamar misalin lu’ulu’u da yake cikin kwasfa.

24. Sakamako ne na abin da suka kasance suna aikatawa.

25. Ba sa kuma jin wani zancen banza da mai sa zunubi a cikinta.

26. Sai dai faɗar salamun-salamun.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, rukunin muminai masu rige-rige zuwa aikata alheri jama’a ne masu yawa a cikin al’ummun farko, watau al’ummun annabawa da manzannin da suka gabaci wannan al’umma ta Musulmi, kuma 'yan kaɗan ne a cikin wannan al’umma ta ƙarshe, watau al’ummar Annabi Muhammad (ﷺ).
Ko kuma ana nufin wannan rukuni na bayin Allah jama’a ne masu yawa a cikin al’ummun farko na wannan al’umma da kuma al’ummun da suka gabace ta, kuma kaɗan ne a cikin al’ummun ƙarshe na wannan al’umma.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakonsu da cewa, su a gidan Aljanna suna kan wasu gadaje ne na alfarma waɗanda aka yi wa ado da zinare, suna kishingiɗe a kansu cikin natsuwa da jin daɗi, suna fuskantar juna cike da soyayya da ƙaunar juna, babu mai juya wa ɗan’uwansa baya. Kuma ga yara ƙanana masu yi musu hidima waɗanda za su dawwama a cikin kamanni ɗaya ba tare da sun tsufa ba ko sun tagayyara, suna kai-komo a kansu ɗauke da kofunan giya marasa mariƙai da butoci masu hannaye da ƙoƙuna cike da giyar Aljanna wadda ba ta yankewa, sannan idan sun sha ta ba ta sa musu ciwon kai kamar giyar duniya, ba kuma ta sa su buguwa ta tafiyar musu da hankulansu har su riƙa yin wasu sumbatu da surutai na banza. Bayan waɗannan kuma su yaran hadimai za su riƙa kewaya su da kayan marmari wanda suka zaɓa suka nuna suna so, da kuma naman tsuntsaye waɗanda ransu yake sha’awa.
Bayan an ba su kayan shaye-shaye da ciye-ciye, sannan kuma suna da matan Hurul-Ini waɗanda aka bayyana kyansu da haskensu da cewa kamar misalin lu’ulu’u ne da yake cikin kwasfansa, iska ko rana ba sa dukan sa sannan babu mai ganin sa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk waɗannan abubuwa da ya tanadar musu sakamako ne a gare su saboda kyawawan ayyukansu da suka kasance suna aikatawa a duniya.
Su kuma ‘yan Aljanna ba abin da za su ji na maganganun banza ko na saɓon Allah, sai dai su riƙa jin sallamar mala’iku a gare su da wadda za su riƙa yi wa junansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin ni’imomin Aljanna da ma’abota dama.

2. Wasu malamai sun ce an ware bishiyar magarya an ambace ta a cikin ni’imomin ‘yan Aljanna domin bishiya ce da Larabawa suke son ta, to amma sai a ƙauyuka ne take tsirowa, don haka ba za su iya dasa ta a cikin lambunansu na gari ba, sai Allah ya bayyana cewa, ya tanadar musu ita a gidan Aljanna don ya ƙara kwaɗaitar da su da janyo hankalinsu.

3. Duk matan gidan Aljanna Allah zai sake musu ƙira cikakkiya ta bai-ɗaya, waɗanda suka haɗa da matan duniya da na Hurul-Ini. Kuma ba za su rasa budurcinsu ba har abada, kamar yadda za su dawwama ababan so ga mazajensu, kuma tsarekun juna koyaushe.

4. Ma’abota dama masu yawa ne a cikin al’ummun farko da wannan al’ummar.

وَأَصۡحَٰبُ ٱلۡيَمِينِ مَآ أَصۡحَٰبُ ٱلۡيَمِينِ ٢٧ فِي سِدۡرٖ مَّخۡضُودٖ ٢٨ وَطَلۡحٖ مَّنضُودٖ ٢٩ وَظِلّٖ مَّمۡدُودٖ ٣٠ وَمَآءٖ مَّسۡكُوبٖ ٣١ وَفَٰكِهَةٖ كَثِيرَةٖ ٣٢ لَّا مَقۡطُوعَةٖ وَلَا مَمۡنُوعَةٖ ٣٣ وَفُرُشٖ مَّرۡفُوعَةٍ ٣٤ إِنَّآ أَنشَأۡنَٰهُنَّ إِنشَآءٗ ٣٥ فَجَعَلۡنَٰهُنَّ أَبۡكَارًا ٣٦ عُرُبًا أَتۡرَابٗا ٣٧ لِّأَصۡحَٰبِ ٱلۡيَمِينِ ٣٨ ثُلَّةٞ مِّنَ ٱلۡأَوَّلِينَ ٣٩ وَثُلَّةٞ مِّنَ ٱلۡأٓخِرِينَ ٤٠

27. Ma’abota hannun dama kuwa, mamakin darajar ma’abota hannun dama!

28. Suna cikin ‘ya’yan itacen magarya marasa ƙaya.

29. Da kuma ayaba mai ‘ya’ya daɓa-daɓa.

30. Da inuwa madawwamiya.

31. Da kuma ruwa mai kwarara.

32. Da ababen marmari masu yawa.

33. Ba masu yankewa ba kuma ba ababen hanawa ba.

34. Da shimfiɗu masu daraja.

35. Lalle Mu ne Muka ƙage su (‘yan matan Aljanna) sabuwar ƙagowa.

36. Sannan Muka sanya su budurwai.

37. Masu begen mazajensu, tsarekun juna.

38. Don ma’abota hannun dama.

39. Su jama’a ne (masu yawa) daga (al’ummun) farko.

40. Kuma jama’a ne (masu yawa) daga (al’ummar) ƙarshe.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon da ya tanadar wa ma’abota hannun dama masu girman daraja a wajensa, da cewa ya tanadar musu Aljanna mai cike da ‘ya’yan itacen magarya marar ƙaya wadda ba za su cutu da ita ba.

An karɓo daga Sulaim ɗan Amir ya ce: Sahabban Manzon Allah sun kasance suna cewa: “Lalle Allah tabbas yakan amfanar da mu ta hanyar tambayoyin mutanen ƙauye.” Ya ce: “Wata rana wani mutumin ƙauye ya zo wurin Manzon Allah (ﷺ) ya ce: ‘Allah mai girma da buwaya ya ambaci wata bishiya mai cutarwa a gidan Aljanna, ni kuma ba na ganin ya dace a sami bishiyar da za ta riƙa cutar da mai ita.’ Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Wacce bishiya ce?” Sai ya ce: “Magarya ce, domin kuwa tana da ƙaya mai cutarwa.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce da shi: “Ba Allah cewa ya yi ba: ‘A cikin ‘ya’yan itacen magarya marasa ƙaya’? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya cire mata ƙayoyinta, ya sanya ɗan itace a mahallin kowace ƙaya, lalle za ta fitar da ‘ya’yanta, kowane ɗaya kuwa zai fitar da launin abinci saba’in da biyu, wanda a cikinsu babu wani launi da ya yi kama da ɗan’uwansa.” [Ibn Abid Dunya, *Sifatul Janna* #105 da Hakim #3778].

Akwai kuma ayaba mai ‘ya’ya goyo-goyo, wasu kan wasu, da kuma inuwa wadda ba ta janyewa da ruwa mai kwarara, shi ne ruwan ƙoramun Aljanna, da kayan marmari masu yawa marasa iyaka, ba sa yankewa har abada, kuma ba su da wani ƙayyadajjen lokaci, babu kuma abin da ya hana a same su duk sanda aka buƙace su. Da kuma shimfuɗu waɗanda aka ɗaga su sama a kan gadaje.
'Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata ni’imar daban da ya tanadar musu a Aljanna, watau matan Hurul-Ini waɗanda ya sake ƙagar halittarsu cikin kyakkyawar sura, ya sanya su ‘yan mata budurwai da babu wani namiji da ya taɓa kusantar su, sannan ya mayar da su ababan soyuwa ga mazajensu kuma tsarekun juna. Ya bayyana cewa, ya tanade su ne ga ma’abota dama waɗanda za su karɓi littattafansu na ayyuka a hannayensu na dama, waɗanda su jama’a ne daga cikin al’ummun annabawan da suka gabata da kuma jama’a daga cikin al’ummar Muhammadu (ﷺ) waɗanda su ne al’umma ta ƙarshe.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Manzon Allah (ﷺ) ya fito wajenmu sai ya ce: “An bijiro mini al’ummomi, sai wani annabi ya zo ya wuce da mutum ɗaya tare da shi, wani annabin kuma da mutum biyu, wani tare da tarin mutane. Wani annabin kuwa ba kowa tare da shi. Sai na hango wani dandazo mai yawa wanda ya tokare sararin sama, sai na yi fatan su zamanto al’ummata ce. Sai aka ce mini: Wannan Musa ne da mutanensa. Sannan aka ce min: Duba ka gani. Sai na ga wani dandazo wanda ya tokare sararin sama. Sai aka sake ce min: Duba can da can. Sai na ga dandazo mai yawa ya tokare sama. Sai aka ce min: Waɗannan al’ummarka ne. Tare da waɗannan kuma akwai mutum dubu saba’in da za su shiga Aljanna ba tare da hisabi ba....” [Bukhari #5752 da Muslim #220].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ma’abota hagu sun ƙunshi duk wani kafiri a duniya, kuma su ne mafi yawan mutane a bayan ƙasa.

2. Bayanin abincin ‘yan wuta da abin shansu; su ma suna ci suna sha, sai dai ba zai amfane su da komai ba sai tsananin azaba.

3. Inuwar wutar Jahannama, wani baƙin hayaƙi ne mai tsananin zafi.

4. Rayuwar ta-more da sharholiya a duniya, tana cikin dalilan da suke sabbaba shiga wuta ranar alƙiyama, domin rayuwa ce da take shagaltar da mai yin ta daga tuna Allah da gode masa da yi masa ɗa’a da jefa mutum cikin aikin saɓon Allah.

5. Dogewa a kan miyagun laifuffuka da rashin tuba da komawa ga Allah, abu ne mai matuƙar haɗari ga bawa.

6. Ranar alƙiyama wani lokaci ne sananne a wurin Allah. Babu wanda ya san sanda za ta zo sai Allah kaɗai.

Suratul Waƙi’a (41-56)
وَأَصۡحَٰبُ ٱلشِّمَالِ مَآ أَصۡحَٰبُ ٱلشِّمَالِ ٤١ فِي سَمُومٖ وَحَمِيمٖ ٤٢ وَظِلّٖ مِّن يَحۡمُومٖ ٤٣ لَّا بَارِدٖ وَلَا كَرِيمٍ ٤٤ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَبۡلَ ذَٰلِكَ مُتۡرَفِينَ ٤٥
وَكَانُواْ يُصِرُّونَ عَلَى ٱلۡحِنثِ ٱلۡعَظِيمِ ٤٦ وَكَانُواْ يَقُولُونَ أَئِذَا مِتۡنَا وَكُنَّا تُرَابٗا وَعِظَٰمًا أَءِنَّا لَمَبۡعُوثُونَ ٤٧ أَوَ ءَابَآؤُنَا ٱلۡأَوَّلُونَ ٤٨ قُلۡ إِنَّ ٱلۡأَوَّلِينَ
وَٱلۡأٓخِرِينَ ٤٩ لَمَجۡمُوعُونَ إِلَىٰ مِيقَٰتِ يَوۡمٖ مَّعۡلُومٖ ٥٠ ثُمَّ إِنَّكُمۡ أَيُّهَا ٱلضَّآلُّونَ ٱلۡمُكَذِّبُونَ ٥١ لَأٓكِلُونَ مِن شَجَرٖ مِّن زَقُّومٖ ٥٢ فَمَالِـُٔونَ مِنۡهَا
ٱلۡبُطُونَ ٥٣ فَشَٰرِبُونَ عَلَيۡهِ مِنَ ٱلۡحَمِيمِ ٥٤ فَشَٰرِبُونَ شُرۡبَ ٱلۡهِيمِ ٥٥ هَٰذَا نُزُلُهُمۡ يَوۡمَ ٱلدِّينِ ٥٦

41. Ma’abota hannun hagu kuma, mamakin ƙasƙancin ma’abota hannun hagu!

42. Suna cikin iska mai tsananin zafi da kuma tafasasshen ruwa.

43. Da kuma inuwa ta turnuƙun hayaƙi.

44. Ba mai sanyi ba, kuma ba mai daraja ba.

45. Lalle su sun kasance masu holewa ne kafin wannan.

46. Sun kuma kasance suna dogewa a kan zunubi mai girma.

47. Sun kuma kasance suna cewa: “Yanzu idan mun mutu, mun zama ƙasa da ƙasusuwa, yanzu lalle za a tashe mu?

48. “Hakanan ma iyayenmu na farko?”

49. Ka ce: “Lalle na farkon da na ƙarshen.

50. “Tabbas za a tattara su zuwa wani lokaci na rana sananniya.

51. “Sannan lalle ku kuma waɗannan ɓatattu masu ƙaryatawa.

52. “Tabbas za ku ci daga bishiyar Zaƙƙumu.

53. “Sannan za ku cika cikunanku da ita.

54. “Sannan za ku sha tafasasshen ruwa a kanta.

55. “Sannan za ku sha irin shan raƙuma masu jin ƙishirwa.”

56. Wannan ita ce gararsu a ranar sakamako.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan sakamakon ‘yan wuta ma’abota hagu, watau waɗanda za a ba su littattafan ayyukansu ta hannun hagu. A ranar lahira suna cikin wata iska mai tsananin zafi wadda za ta yi matuƙar addabar su, idan sun buƙaci ruwan sha kuwa sai dai su sha wani tafasasshen ruwa wanda yake tsittsinka musu ‘ya’yan hanji. Ba kuma za su sami wata inuwa ba sai inuwar wani turnuƙaƙƙen baƙin hayaƙi wanda ba ya da iska mai daɗi, ga shi kuma ba ya da kyan gani. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abin da ya kai ‘yan wuta cikin wannan mummunar azabar da cewa su sun kasance a duniya suna rayuwa irin ta ta-more da sharholiya ba abin da suka sa a gaba sai biyan buƙatun sha’awarsu, kuma ga uwa-uba sun kasance masu dogewa a kan babban laifi na kafirci da bautar abin da ba Allah ba, ga shi kuma suna ƙaryata ranar alƙiyama suna cewa babu wata rayuwa bayan mutuwa, har ma suna mamakin cewa, ta yaya bayan sun riga sun mutu sun zama ƙasa da rududdugaggun ƙasusuwa a ce kuma za a tayar da su da ransu, kuma wai ba ma su ba har da iyayensu na farko waɗanda sun shafe shekaru aru-aru da mutuwa a ce su ma za a tashe su, don haka suna ganin wannan batu ba gaskiya ne ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) cewa, ya mayar musu da martani na cewa, lalle su sani duk mutanen farko da na ƙarshe gaba ɗayansu za a tashe su a tattara su wuri guda a ranar alƙiyama,

ranar da Allah ya sanya mata wani lokaci ƙayyadadde da za ta zo a cikinsa, don ya yi musu hisabi da sakamako.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa waɗannan masu ƙaryata ranar alƙiyama irin mummunan sakamakon da za su gamu da shi a ranar yayin da za a jefa su wuta, abincinsu kuma ‘ya’yan itaciyar Zaƙkum ne, bishiya mafi muni da sharri a wutar Jahannama, su ci har su take cikinsu da ita ba kuma tare da ta yi musu maganin yunwa ba. Sannan abin shansu shi ne tafasasshen ruwa, wanda za su yi ta kwankwaɗar sa kamar yadda raƙuma masu fama da cutar ƙishirwa suke kwankwaɗar ruwa, ba kuma tare da ya yi musu maganin ƙishi ba sai dai ya tsittsinka musu ‘yan hanji.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa wannan mummunan abinci da za su ci da tafasasshen ruwan da za su sha a ranar alƙiyama ita ce liyafar da aka tanadar musu. Wannan magana ce ta gatse da ba’a mai ƙara cusa musu haushi da baƙin ciki a ransu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karyatawar mushirikai da tashi bayan mutuwa ta nuna kamar ba su yarda cewa Allah ne ya halicce su ba, shi ya sanya Allah ya tunatar da su hakan.

2. In da gaske ne kamar yadda mushirikai suka ce, babu yadda za a yi rududdugaggun ƙasusuwa su dawo masu rai, to da sai kuma su ce mataccen maniyyi ba zai taɓa zama mutum mai rai ba.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara faruwar mutuwa domin tashi daga rayuwar duniya mai gushewa zuwa rayuwar lahira ta har abada. Sannan mutuwa tana ƙara tuna wa bawa cikar ilimin Allah da Kudurarsa.

4. Mutuwa tana yawo ne a tsakanin halittu daga wannan zuwa wancan, babu mai iya kuɓuce mata, sannan babu wasu shekaru ko yanayi na musamman da sai a cikinsu take aukuwa, watau mutuwa kamar wani ajiyayyen abu ne don rabawa ga mutane, babu wanda ya san lokacin da zai sami kasonsa.

5. Saukar da ruwa daga sama da fitar da tsirrai daga ƙasa da wutar kunnawa da mutane suke amfana da ita, duk waɗannan wasu ni’imomin Allah ne da ya wajaba ga bayinsa su gode masa a kansu Allah kuma yana iya ya raba su da su duk sanda ya ga dama.

Suratul Waƙi’a (57-74)
نَحۡنُ خَلَقۡنَٰكُمۡ فَلَوۡلَا تُصَدِّقُونَ ٥٧ أَفَرَءَيۡتُم مَّا تُمۡنُونَ ٥٨ ءَأَنتُمۡ تَخۡلُقُونَهُۥٓ أَمۡ نَحۡنُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٥٩ نَحۡنُ قَدَّرۡنَا بَيۡنَكُمُ ٱلۡمَوۡتَ وَمَا نَحۡنُ
بِمَسۡبُوقِينَ ٦٠ عَلَىٰٓ أَن نُّبَدِّلَ أَمۡثَٰلَكُمۡ وَنُنشِئَكُمۡ فِي مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٦١ وَلَقَدۡ عَلِمۡتُمُ ٱلنَّشۡأَةَ ٱلۡأُولَىٰ فَلَوۡلَا تَذَكَّرُونَ ٦٢ أَفَرَءَيۡتُم مَّا تَحۡرُثُونَ ٦٣
ءَأَنتُمۡ تَزۡرَعُونَهُۥٓ أَمۡ نَحۡنُ ٱلزَّٰرِعُونَ ٦٤ لَوۡ نَشَآءُ لَجَعَلۡنَٰهُ حُطَٰمٗا فَظَلۡتُمۡ تَفَكَّهُونَ ٦٥ إِنَّا لَمُغۡرَمُونَ ٦٦ بَلۡ نَحۡنُ مَحۡرُومُونَ ٦٧ أَفَرَءَيۡتُمُ ٱلۡمَآءَ ٱلَّذِي
تَشۡرَبُونَ ٦٨ ءَأَنتُمۡ أَنزَلۡتُمُوهُ مِنَ ٱلۡمُزۡنِ أَمۡ نَحۡنُ ٱلۡمُنزِلُونَ ٦٩ لَوۡ نَشَآءُ جَعَلۡنَٰهُ أُجَاجٗا فَلَوۡلَا تَشۡكُرُونَ ٧٠ أَفَرَءَيۡتُمُ ٱلنَّارَ ٱلَّتِي تُورُونَ ٧١ ءَأَنتُمۡ
أَنشَأۡتُمۡ شَجَرَتَهَآ أَمۡ نَحۡنُ ٱلۡمُنشِـُٔونَ ٧٢ نَحۡنُ جَعَلۡنَٰهَا تَذۡكِرَةٗ وَمَتَٰعٗا لِّلۡمُقۡوِينَ ٧٣ فَسَبِّحۡ بِٱسۡمِ رَبِّكَ ٱلۡعَظِيمِ ٧٤

57. Mu ne Muka halicce ku, me ya sa ba kwa gaskatawa?

58. Ba kwa ganin maniyyi da kuke zubawa.

59. Shin ku ne kuke halittar sa, ko kuwa Mu ne Masu halittar?

60. Mu ne Muke ƙaddara mutuwa a tsakaninku, kuma Mu ba Masu gajiyawa ba ne.

61. A kan Mu musanya irinku Mu kuma halitta ku cikin abin da ba ku sani ba.

62. Haƙiƙa kuma ku kun san halitta ta farko, don me ba kwa wa'azantuwa?

63. Ku ba Ni labarin abin da kuke nomawa?

64. Shin ku ne kuke tsiro da shi, ko Mu ne Masu tsirarwar?

65. Idan da Mun ga dama tabbas da Mun mayar da shi karmami, sai ku wayi gari kuna mamaki.

66. (Kuna cewa): "Lalle mu an ɗora mana asara."

67. "A'a, mu dai an hana mu ne."

68. Ku ba Ni labarin ruwa wanda kuke sha.

69. Yanzu ku ne kuke sauko da shi daga girgije, ko kuwa Mu ne masu saukarwar?

70. Da Mun ga dama da Mun mayar da shi (ruwa) mai zartsi, to don me ba kwa godewa?

71. Ku ba Ni labarin wutar da kuke kunnawa.

72. Yanzu ku ne kuka halicci bishiyarta, ko kuwa Mu ne Masu halittar?

73. Mu ne Muka sanya ta wa'azi da kuma abin amfani ga matafiya.

74. Saboda haka sai ka tsarkake Sunan Ubangijinka Mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mushirikai masu ƙaryata tashi bayan mutuwa ƙarfafan hujjoji da suke tabbatar da yiwuwar dawo da matattu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalinsu a kan abubuwa bakwai waɗanda suke tabbatar da cikar Kudurar Allah game da sake dawo da matattu.
Na farko, Allah ya tabbatar musu cewa, shi ne ya samar da su daga babu, ya halicce su suka zama mutane, to me zai hana su su gaskata cewa zai iya dawo da halittarsu bayan mutuwarsu?
Na biyu, su dubi ruwan maniyyi da suke sanyawa a mahaifar matansu wanda daga bisani ake halittar mutum da shi, shin su ne suka halicci wannan maniyyin ko kuwa Allah ne ya halicce shi? Babu shakka sun san ba su ne suka halicce shi ba, wannan aikin Allah ne shi kaɗai, to yanzu mai irin wannan Kudurar sai ya kasa dawo da matattu bayan sun zama ƙasa?!
Na uku, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, shi ne ya ƙaddara mutuwa a tsakaninsu, kowanne ɗaya daga cikinsu yana da ajalinsa wanda ba zai rigaye shi ba, ba kuma zai wuce shi ba. Idan har sun yarda shi ne yake da ikon karɓe rayuwarsu su mutu, to me zai hana su yarda zai iya dawo musu da rayukansu su sake tashi bayan sun mutu?! Don haka ba za su gagare shi ba a kan ya musanya tsarin halittarsu daga yadda suka san ta, ya sake halittar su a cikin wata surar da ba su sani ba. Yanzu wannan kaɗai ba zai sanya su su wa'azantu ba?

Na huɗu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tabbatar musu cewa, sun riga sun san yadda ya halicce su a karon farko, to ashe ba za su ɗau izina ba a kan cewa wanda ya yi halitta a karon farko yana da cikakken ikon ya tashe su da rai bayan sun mutu?
Na biyar, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalinsu zuwa ga lura da irin da suke shukawa a cikin ƙasa ya fito ya zama shuka, to shin su ne suke fito da wannan shukar ko kuma Allah ne yake fito da ita ta girma ta yi 'ya'ya wanda shi ne suke girba su ci su kuma ciyar da dabbobinsu? Babu shakka Allah ne kawai mai yin wannan aiki, ba shi da abokin tarayya. To me zai hana shi ikon sake dawo da matattu ya busa musu rai su tashi, kamar yadda ya busa wa wannan iri rai ya fito ya zama shuka? Kuma da ya ga dama da ita kanta shukar bayan ta fito da sai ya mayar da ita duddugar karmami tun kafin ta nuna su girbi amfaninsu, sai kuma su wayi gari suna mamakin abin da ya faru da shukarsu, suna cewa sun tabka hasara, wasu kuma suna cewa, a'a an dai hana su ne su amfana da shukarsu.
Na shida, ya ja hankalinsu zuwa ga ruwan da suke sha, ya tambaye su cewa, shin su ne suka saukar da shi daga girgije ko kuwa Allah ne ya saukar da shi? Babu shakka sun san yin haka aikin Allah ne shi kaɗai mai iko a kan komai. Da kuma ya ga dama sai ya mayar da ruwan ya zama na zartsi ya gagara shayuwa kuma ya ƙi amfani wajen ban-ruwa, to amma sai ya ni'imta su da ruwa mai daɗin kwankwaɗa mai amfani a gare su da kuma dabbobinsu da shuke-shukensu, to don me ba za su riƙa gode wa Allah ba, su yi imani da cikar Kudurarsa a kan komai har da tashin matattu don yi musu hisabi?
Na bakwai, ya sake jan hankalinsu game da wutar da suke kunnawa domin buƙatunsu daban-daban, ya tambaye su, ko shin su ne suka halicci bishiyar da ake hura wutar da ita, ko kuma Allah ne ya tausaya musu ya fito musu da ita? Su dai sun tabbatar ba aikinsu ba ne, aikin Allah ne shi kaɗai, to me ya hana su gaskata Kudurarsa ta sake dawo da halittu bayan mutuwa?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, shi ne ya sanya wannan wutar ta duniya ta zama tunatarwa game da wutar lahira, kuma ta kasance mai amfani ga matafiya daga cikinsu a nan duniya.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wutarku ta duniya kaso ɗaya ne daga cikin kaso saba'in na wutar Jahannama, kuma sai da aka nutsar da ita a cikin kogi sau biyu, ba don haka ba da Allah bai sanya wani amfani a cikinta ga wani ba." [Ahmad #7327].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa da ya tsarkake Ubangijinsa mai girma daga duk wani abu da bai dace da shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da ikon ya yi rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittunsa. Amma ba ya halatta ga wani Musulmi ya yi rantsuwa sai da Allah kaɗai.

2. Girman darajar Alƙur'ani da tabbatar da cewa daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake babu kokwanto a cikinsa.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsare littafinsa babu wani shaiɗani da zai iya kusantar sa ballantana har ya shigar da wani abu a cikinsa.

4. Al'adar jahiliyya ce jingina wa taurari wani tasiri wajen saukar ruwan sama.

Suratul Waƙi’a (75-82)

۞فَلَآ أُقۡسِمُ بِمَوَٰقِعِ ٱلنُّجُومِ ٧٥ وَإِنَّهُۥ لَقَسَمٞ لَّوۡ تَعۡلَمُونَ عَظِيمٌ ٧٦ إِنَّهُۥ لَقُرۡءَانٞ كَرِيمٞ ٧٧ فِي كِتَٰبٖ مَّكۡنُونٖ ٧٨ لَّا يَمَسُّهُۥٓ إِلَّا ٱلۡمُطَهَّرُونَ ٧٩ تَنزِيلٞ مِّن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٨٠ أَفَبِهَٰذَا ٱلۡحَدِيثِ أَنتُم مُّدۡهِنُونَ ٨١ وَتَجۡعَلُونَ رِزۡقَكُمۡ أَنَّكُمۡ تُكَذِّبُونَ ٨٢

75. To ina yin rantsuwa da mafaɗar taurari.

76. Lalle ita kuwa rantsuwa ce mai girma, da kuna ganewa.

77. Lalle shi Alƙur’ani ne mai girma.

78. A cikin littafi abin kiyayewa (daga wani sauyi).

79. Babu mai taɓa shi sai tsarkakakku.

80. Saukakke ne daga Ubangijin talikai.

81. Yanzu wannan zance kuke ƙaryatawa?

82. Kuke kuma sanya (godiyar) arzikinku shi ne ku riƙa ƙaryatawa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da kafirai cewa Alƙur’ani mai girma gaskiya ne, inda ya yi musu rantsuwa da wuraren taurari da mafaɗarsu. Ya tabbatar musu cewa, lalle wannan rantsuwa ce mai girma, domin taurari da tafiyarsu a sararin sama abu ne da ke cike da ayoyi da darussa masu ɗimbin yawa. Ya kuma yi wannan rantsuwa ne don ya tabbatar musu cewa, abin da suke ji ana karanta musu Alƙur’ani ne mai girma, domin ya ƙunshi alheri mai yawa, da ɗimbin ilimi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da shi da farko a cikin Lauhul Mahafuzu wanda aka kiyaye shi babu mai ganin sa. Babu kuma mai taɓa wannan Alƙur’ani sai mala’iku tsarkakakku, watau waɗanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkake su daga dukkan zunubai da aibubbuka. Alƙur'ani saukakke ne daga Ubangijin halittu zuwa ga Annabi Muhammadu (ﷺ)Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi kafirai cewa, yanzu wannan Alƙur’ani shi suke ƙaryatawa suna faɗar maganganu marasa kyau a kansa? Sannan maimakon su gode wa Allah bisa arzikin da ya ba su sai su riƙa ƙaryata shi, suna danganta wasu ni’imominsa kamar ruwan sama, zuwa ga wasu halittunsa, kamar taurari, suna cewa tauraro kaza ne ya yi musu ruwa?

An ƙarɓo daga Zaid ɗan Khalid Al-Juhami (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya yi mana sallar asuba a Hudaibiyya bayan an kwana ana ruwa. Bayan ya gama salla sai ya fuskanto mutane ya ce musu: “Shin kun san abin da Ubangijinku ya faɗa?” Sai suka ce: “Allah da Manzonsa ne mafiya sani.” Sai ya ce: “Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: “Daga cikin bayina wani ya wayi gari yana mai imani da ni wani kuma yana kafirce mini. Amma wanda ya ce: “An yi mana ruwa da falalar Allah da rahamarsa, to wannan mai imani ne da ni; wanda kuma ya ce: “An yi mana ruwa da tauraro kaza da kaza, to wannan ya kafirce mini, ya kuma yi imani da tauraro.” [Bukhari #846 da Muslim #17061].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daga cikin ɗalilai masu nuna cikar Kudurar Allah a kan raya matattu, shi ne ganin yadda yake cire rai daga gangar jiki a lokacin da babu mai iya dawo da shi. Wannan ya tabbatar da cewa, Allah ya yi haka ne

don wata hikimar da ya ƙaddara, domin ba don gudanar da sakamako ga halittu ba da babu wata hikimar raba su da rayukansu sun ƙi ko sun so.

2. Tabbatar da aukuwar tsananin magagin mutuwa ga ɗan’adam wadda ba zai iya magance wa kansa ita ba.

3. Asali mutane ba za su iya ganin mala’ika ba sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya so haka don wata hikimarsa.

4. Girman sakamakon makusanta ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Waƙi’a (83-96)
فَلَوۡلَآ إِذَا بَلَغَتِ ٱلۡحُلۡقُومَ ٨٣ وَأَنتُمۡ حِينَئِذٖ تَنظُرُونَ ٨٤ وَنَحۡنُ أَقۡرَبُ إِلَيۡهِ مِنكُمۡ وَلَٰكِن لَّا تُبۡصِرُونَ ٨٥ فَلَوۡلَآ إِن كُنتُمۡ غَيۡرَ مَدِينِينَ ٨٦
تَرۡجِعُونَهَآ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٨٧ فَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلۡمُقَرَّبِينَ ٨٨ فَرَوۡحٞ وَرَيۡحَانٞ وَجَنَّتُ نَعِيمٖ ٨٩ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلۡيَمِينِ ٩٠ فَسَلَٰمٞ
لَّكَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلۡيَمِينِ ٩١ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ٱلضَّآلِّينَ ٩٢ فَنُزُلٞ مِّنۡ حَمِيمٖ ٩٣ وَتَصۡلِيَةُ جَحِيمٍ ٩٤ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ حَقُّ ٱلۡيَقِينِ ٩٥
فَسَبِّحۡ بِٱسۡمِ رَبِّكَ ٱلۡعَظِيمِ ٩٦

83. Me ya hana idan (rai) ya isa maƙogwaro.

84. Ku kuma a lokacin kuna kallo.

85. Mu ne kuwa Muka fi ku kusanci da shi, sai dai kuma ba kwa gani.

86. Me ya hana idan da kun zamanto ba waɗanda za a tasa ba ne.

87. Ku dawo da shi (ran) mana idan kun kasance masu gaskiya.

88. Amma kuma idan (mai mutuwar) ya kasance daga makusanta.

89. To (sakamakonsa) hutu ne da arziki mai daɗi, da kuma Aljannar ni’ima.

90. Idan kuma ya kasance daga ma’abota hannun dama ne.

91. To aminci ya tabbata a gare ka don zamanka na hannun dama.

92. Idan kuwa ya kasance daga masu ƙaryatawa ne ɓatattu.

93. To kaɓaki ne na tafasasshen ruwa (sakamakonsa).

94. Da kuma shiga wutar Jahannama.

95. Lalle wannan (bayani na cikin wannan Surar) shi ne haƙiƙanin gaskiya.

96. To ka yi tasbihi da tsarkake sunan Ubangijinka mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci kafirai masu ƙaryata zuwan ranar alƙiyama da hisabi a kan ayyukan bayi, da cewa me ya hana su lokacin da suka ga ɗayansu yana kakarin mutuwa, ransa ya zo maƙoshi zai fita, me ya sa ba za su hana ran fita ba, su dawo da shi cikin jikin wannan ɗan'uwa nasu, idan har su masu gaskiya ne cewa, babu tashi bayan mutuwa, kuma babu hisabi? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, a lokacin ya fi su kusanci da wannan ɗan'uwa nasu da iliminsa da Kudurarsa da mala'ikunsa, kawai dai ba sa ganin mala'ikun ne.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda mutane za su kasu kashi uku yayin da suka zo mutuwa.
Na farko, idan mamacin yana daga cikin bayin Allah ne masu rige-rige wajen aikin alheri, makusanta ga Allah, waɗanda suka aikata abubuwan da aka wajabta musu har da mustahabbi, suka guje wa abubuwan da aka hana su har ma da makaruhi, to waɗannan suna da sakamakon hutu babu wahala tare da su da kuma arziki mai daɗi da rahama da gidan Aljanna. Za su sami duk ni'imar da suke sha'awa a cikinta.
Na biyu, idan kuwa mamacin yana daga ma'abota hannun dama ne, waɗanda suka aikata wajibi suka kuma guje wa haramun, amma suka samu gazawa a wasu al'amuransu na addini ko na rayuwa, to waɗannan za a riƙa faɗa wa ɗayansu cewa amincin ya tabbata a gare shi, yana cikin ma'abota hannun dama.
Na uku, idan mamacin yana daga cikin masu ƙaryata abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi, watau ɓatattu waɗanda suka kauce wa tafarki madaidaici, to kaɓakin da za a tare shi da shi, shi ne tafasasshen ruwa da ƙonawa da wutar Jahannama.
A ƙarshen Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa wannan labari da yake ba shi tabbas shi ne haƙiƙanin gaskiya da babu sofanen shakka a cikinta, don haka ya umarce shi da ya tsarkake sunan Ubangijinsa mai girma da yi masa tasbihi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cewa, ba mutum da aljani ne kawai suke bautar Allah ba, duk wani abu a sama ko a ƙasa masu bautar Allah ne tare da tsarkake shi daga duk wani aibi ko tawaya.

2. Tabbatar da cikar ikon Allah da Kudurarsa a kan komai.

3. Tabbatar da cewa, Allah shi ne na farko wanda farkonsa ba ya da fari, watau yana nan tun fil azal. Shi ne kuma na ƙarshe wanda zai wanzu bayan komai ya halaka. Shi ne kuma bayyananne wanda duk wani abu yana nuna samuwarsa da Kaɗaitakarsa. Shi ne kuma ɓoyayye wanda babu mai iya riskar haƙiƙanin Zatinsa ko siffarsa.

4. Tabbatar da daidaiton Allah a kan Al'arshinsa daidaito wanda ya dace da shi.

5. Ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kewaye bayinsa gaba ɗaya, yana tare da su da iliminsa da ikonsa.

6. Tabbatar da zuwan alƙiyama

57-Suratul Hadid

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunanta '*Suratul Hadid* ' kamar yadda ya zo a littattafan tafsiri da hadisi. An kuma kira ta da wannan suna ne saboda lafazin 'Al-hadid' ya zo a cikinta a aya ta 25, ma'anarsa kuma shi ne baƙin ƙarfe.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai sun tabbatar da cewa, Sura ce Madaniyya. Sai dai a cikinta akwai wasu ayoyi da ake ganin *Makiyya* ne, watau daga farkon Surar har zuwa aya ta 9 da kuma aya ta 16.
An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya kara masa yarda) ya ce: "Shekara huɗu ne tsakanin lokacin da muka musulunta zuwa lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zarge mu da wannan ayar: (Yanzu lokaci bai yi ba ga waɗanda suka yi imani zukatansu su yi taushi da zikirin Allah...?)." [Muslim #3027]. Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya kara masa yarda) yana daga cikin Musulmin farko da suka fara shiga Musulunci.

3. Jerin Saukarta
Ita ce Sura ta tis'in da biyar (95) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Zalzala*' kafin '*Suratu Muhammad*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin da tara ne (29) a lissafin malaman Basra da Kufa. Amma a lissafin malaman Madina da Makka da Sham adadinsu ashirin da takwas ne (28).

5. Babban Jigonta:
Kwaɗaitar da al'ummar Musulmi a kan tashi tsaye wajen gina kanta da imani da ƙarfin soja da na tattalin arzuki don ɗaukaka addinin Allah da guje wa dulmiya cikin son duniya da kwaɗayinta.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tunatarwa game da girman Allah da ɗaukakar siffofinsa da cikar Kudurarsa da ikonsa a kan komai, da yalwar iliminsa da imani da samuwarsa, da kuma yin imani da abin da Manzonsa (ﷺ) ya zo da shi.
• Faɗakarwa game da abin da Alƙur'ani ya ƙunsa na shiriya da nuna hanyar tsira, da tunatarwa game da rahamarsa da tausayinsa ga bayinsa.
• Kwaɗaitarwa game da ciyar da dukiya don Allah da nuna wa mutane cewa, dukiya wani abu ne mai gushewa, babu abin da mutum zai mora daga cikinta sai abin da ya bayar don Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadar wa muminai maza da mata ranar alƙiyama, da kuma azabar da ya tanadar wa munafukai maza da mata a wannan ranar.
• Gargaɗin muminai game da faɗawa cikin irin abin da ma'abota littafi suka faɗa cikinsa na ƙeƙashewar zukata sakamakon watsi da suka yi da shiriyar Allah da manzanninsu suka zo musu da ita.
• Tunatarwa game da tashin alƙiyama.

• Jan hankali a kan guje wa ruɗuwa da ƙyale-ƙyalen duniya mai saurin gushewa.
• Umarni da yin haƙuri da bayanin hikimar aika manzanni da saukar da littattafai, watau shi ne tabbatar da adalci a tsakanin mutane.
• Kwatanta manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ) da na Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da nuna cewa, a cikin zurriyar kowannensu akwai shiryayyu akwai kuma fasiƙai. Hakanan kuma Allah ya aiko Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a bayansu, shi ma wasu suka bi shi, wasu kuma suka kafirce masa.
• Kira ga muminai da su tsantsanta imaninsu ga Allah kaɗai da yi musu alƙawari da samun kyakkyawan sakamako a ranar alƙiyama da nuna musu cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fifita su a kan sauran al'ummu, wannan kuwa wata falala ce daga gare shi yana bayar da ita ga wanda ya ga dama.

Suratul Hadid (1-6)

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١ لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ٢ هُوَ ٱلۡأَوَّلُ وَٱلۡأٓخِرُ وَٱلظَّٰهِرُ وَٱلۡبَاطِنُۖ وَهُوَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٌ ٣ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ يَعۡلَمُ مَا يَلِجُ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا يَخۡرُجُ مِنۡهَا وَمَا يَنزِلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ وَمَا يَعۡرُجُ فِيهَاۖ وَهُوَ مَعَكُمۡ أَيۡنَ مَا كُنتُمۡۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ٤ لَّهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ ٥ يُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِۚ وَهُوَ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Abin da yake cikin sammai da ƙasa ya yi tasbihi ga Allah; Shi ne kuma Mabuwayi, Mai hikima.

2. Mulkin sammai da ƙasa nasa ne; Yana rayawa, Yana kuma kashewa; kuma Shi Mai iko ne a kan komai.

3. Shi ne Na farko kuma Na ƙarshe, kuma Bayyananne kuma Ɓoyayye; Shi kuma Masanin komai ne.

4. Shi ne wanda Ya halicci sammai da ƙasa cikin kwana shida, sannan Ya daidaitu a kan Al'arshi. Yana sane da abin da yake shiga cikin ƙasa da abin da yake fitowa daga cikinta, da kuma abin da yake saukowa daga sama da abin da yake hawa cikinta; kuma Shi Yana tare da ku a duk inda kuka kasance. Allah kuwa Mai ganin duk abin da kuke aikatawa ne.

5. Mulkin sammai da ƙasa nasa ne. Kuma ga Allah ake mayar da al'amura.

6. Yana shigar da dare cikin rana, Yana kuma shigar da rana cikin dare. Kuma Shi Masanin abubuwan da suke cikin ƙiraza ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da sanar da bayinsa cewa, duk abubuwan da suke cikin sammai da na ƙasa sun tsarkake shi da yi masa tasbihi, kuma shi ne Mabuwayi wanda babu mai iya ja da shi, mai hikima a cikin halittarsa da shari'arsa da ƙaddararsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mulkin sammai da ƙasa duka nasa ne, shi ne yake raya wanda ya ga damar rayawa, yake kuma kashe duk wanda ya ga damar kashewa, babu mai iya hana shi aikata abin da ya so, kuma shi mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi.
Sai kuma ya bayyana cewa, shi ne na farko, watau babu wani abu gabaninsa, shi ne kuma na ƙarshe, watau babu wani abu bayansa, shi ne kuma bayyananne, watau babu wani abu sama da shi, kuma shi ne ɓoyayye, watau babu wani abu da ya fi shi ɓuya, kuma shi masanin komai ne na sarari da na ɓoye.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Faɗima (Allah ya ƙara mata yarda), ta zo wajen Manzon Allah (ﷺ) tana roƙon sa ya ba ta hadima, sai ya ce mata: “Ki ce: Ya Allah, Ubangijin sammai bakwai, kuma Ubangijin Al’arshi mai girma, kuma Ubangijinmu, kuma Ubangijin komai, wanda ya saukar da Attaura da Linjila da Alƙur’ani, wanda ya fitar da ƙwaya da ƙwallon dabino, ina neman tsarinka daga sharrin duk wani abu wanda kai ne kake riƙe da makwarkwaɗarsa. Kai ne na farko babu wani abu gabaninka, kuma kai ne na ƙarshe babu wani abu bayanka, kai ne kuma bayyananne babu wani abu sama da kai, kai ne kuma ɓoyayye babu wani abu da ya fi ka ɓuya, ka biya mana bashi, ka kuma raba mu da talauci.” [Muslim #2713].

A wata ruwayar: Annabi (ﷺ) ya kasance yana karanta wannan addu’ar yayin da ya zo kwantawa barci. [Muslim #2713].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, shi ne ya halicci sammai da ƙasa a cikin kwanaki shida, ya fara ranar Lahadi ya kuma ƙare ranar Juma’a, duk kuwa da cewa yana da ikon halittar su cikin ƙasa da ƙiftawar ido. Sannan ya daidaita a kan Al’arshi daidaiton da ya dace da shi. Yana sane da duk abin da yake shiga cikin ƙasa na ruwan sama da irin shuka da makamantansu, yana kuma sane da abin da yake fita daga cikin ƙasa, kamar tsirrai da ma’adanai da makamantansu. Yana kuma sane da duk abin da yake saukowa daga sama, kamar ruwa da wahayi da sauransu, yana kuma sane da abin da yake hawa zuwa sama, kamar mala’iku da ayyukan bayinsa da rayukansu. Ya tabbatar wa da bayinsa cewa yana tare da su a duk inda suke, watau da iliminsa, babu wani abu da yake ɓuya a gare shi, yana kuma ganin duk abin da suke aikatawa, zai kuma yi musu sakayya a kansa, domin kuwa duk mulkin sammai da ƙasa nasa ne shi kaɗai, kuma zuwa gare shi ne za a mayar da duk al’amura, inda zai yi wa bayinsa hisabi a ranar alƙiyama, ya saka wa kowa gwargwadon aikinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sake tabbatar da cikar Kudurarsa da yalwar iliminsa, da cewa shi ne yake shigar da dare cikin yini don tsawonsa ya ragu shi kuma yini ya ƙara tsawo, wani lokaci kuma ya shigar da yini cikin dare domin tsawonsa ya ragu shi kuma dare ya ƙaru. Allah masanin abin da yake cikin ƙirazan bayinsa ne, babu abin da za su iya ɓoye masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fara yin umarni da imani sannan ya yi umarni da ciyar da dukiya saboda shi, domin ciyarwa don Allah ba za ta samu ba sai tare da imani da Allah, sannan wanda ya yi imani da Allah shi ne aikinsa na ƙwarai zai amfane shi ranar alƙiyama.

2. Dukiyoyi na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne, duk wanda ya sanya wani abu na dukiya a hannunsa, to wakilci ne aka ba shi, dole ne ya tafiyar da wannan dukiyar ta hannunsa kamar yadda Allah yake so ya kuma umarce shi.

3. Ladan ciyar da dukiya don Allah babban abu ne a wurin Allah.

4. Babbar baiwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa bayinsa da ya aiko musu Manzonsa (ﷺ), ya saukar musu da littafinsa mai ɗauke da ayoyi bayyanannu domin karantar da su hanyar shiriya. Wannan rahama ce babba daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Duk wani abu na duniya mai gushewa ne daga hannun mai shi wata rana, Allah ne kaɗai zai gaje duk abin da yake sammai da wanda yake ƙasa, domin da man nasa ne alal-haƙiƙa. To duk wanda zai yi la’akari da haka ba zai ji wuyar fitar da dukiyarsa ya bayar don Allah ba.

6. Fifikon darajojin sahabban Manzon Allah duk kuwa da cewa gaba ɗayansu ‘yan Aljanna ne. Wanda daga cikinsu ya ciyar da dukiyarsa ya yi yaƙi tare da Manzon Allah (ﷺ) tun gabanin buɗe Makka ba zai yi daidai da sahabin da bai samu yin haka ba, domin Musulmi kafin Fat'hu Makka sun kasance cikin wani matsanancin yanayi, a wannan lokacin babu masu yin imani sai muminai na gasken gaske. Amma bayan buɗe Makka Musulunci ya yi ƙarfi sosai, kuma mutane dodo-dodo sun yi ta karɓar addinin Allah, don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fifita sahabban farko a kan waɗanda suka shiga Musulunci daga baya.

7. Yawancin Malaman tafsiri sun fassara '*Fat'hu*' a wannan ayar da cewa ana nufin *Fat'hu Makka*, amma an samu wasu daga cikinsu, kamar Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) da Sha'abi suna ganin cewa, ana nufin Sulhul Hudaibiyya ne da wannan ayar, domin shi ma wannan sulhu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira shi da sunan '*Fat'hu*', kamar yadda ya zo a ayar farko ta '*Suratul Fat'hi*'. Malam Ibn Jarir Aɗ-Ɗabari da Shaikhul Islam Ibn Taimiyya sun goyi bayan wannan ra'ayi na biyu, sun kuma kafa hujja a kansa da hadisin Anas (Allah ya ƙara masa yarda) inda ya ce: Wata magana ta shiga tsakanin Khalid ɗan Walid da Abdurrahman ɗan Aufu, sai Khalid ya ce wa Abdurrahman: “Kuna mana alfahari don kun riga mu musulunta da wasu kwanaki!” Sai wannan magana ta Khalid (Allah ya ƙara masa yarda) ta je kunnen Manzon Allah (ﷺ), sai ya ce: "Ku ƙyale min sahabbaina, na rantse da wanda raina yake hannunsa da a ce ɗayanku zai ciyar da kamar dutsen Uhudu – ko duwatsu - na zinari, ba za ku cim ma ayyukansu ba." [Ahmad#13812].

Wannan Hadisin ya nuna mararrabar ita ce Sulhul Hudaibiyya, domin Khalid wanda wannan abu ya faru da shi ya Musulunta ne bayan Sulhul Hudaibiyya kafin *Fat'hu Makka*.

8. Duk wanda zai bayar da taimakonsa lokacin da ake cikin tsananin buƙata, kamar wanda zai ciyar da dukiyarsa lokacin da ake tsaka da yunwa ya fi wanda zai ba da dukiyarsa lokacin da ake cikin walwala, ko ake ƙarancin buƙata.

Suratul Hadid (7-11)

ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَأَنفِقُواْ مِمَّا جَعَلَكُم مُّسۡتَخۡلَفِينَ فِيهِۖ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡ وَأَنفَقُواْ لَهُمۡ أَجۡرٞ كَبِيرٞ ٧ وَمَا لَكُمۡ لَا تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلرَّسُولُ يَدۡعُوكُمۡ لِتُؤۡمِنُواْ بِرَبِّكُمۡ وَقَدۡ أَخَذَ مِيثَٰقَكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٨ هُوَ ٱلَّذِي يُنَزِّلُ عَلَىٰ عَبۡدِهِۦٓ ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٖ لِّيُخۡرِجَكُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ بِكُمۡ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ ٩ وَمَا لَكُمۡ أَلَّا تُنفِقُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلِلَّهِ مِيرَٰثُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ لَا يَسۡتَوِي مِنكُم مَّنۡ أَنفَقَ مِن قَبۡلِ ٱلۡفَتۡحِ وَقَٰتَلَۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَعۡظَمُ دَرَجَةٗ مِّنَ ٱلَّذِينَ أَنفَقُواْ مِنۢ بَعۡدُ وَقَٰتَلُواْۚ وَكُلّٗا وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلۡحُسۡنَىٰۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ١٠ مَّن ذَا ٱلَّذِي يُقۡرِضُ ٱللَّهَ قَرۡضًا حَسَنٗا فَيُضَٰعِفَهُۥ لَهُۥ وَلَهُۥٓ أَجۡرٞ كَرِيمٞ ١١

7. Ku yi imani da Allah da kuma Manzonsa, ku kuma ciyar daga abin da ya sanya ku wakilai a kansa, to waɗanda suka yi imani daga cikinku, suka kuma ciyar suna da lada mai girma.

8. Kuma me ya same ku ne ba kwa yin imani da Allah, alhali kuwa Manzo yana kiran ku don ku yi imani da Ubangijinku, haƙiƙa kuma kun yi masa alƙawari, in dai kun kasance muminai.

9. Shi ne Wanda Yake saukar da ayoyi bayyanannu ga Bawansa don Ya fitar da ku daga duffai zuwa haske. Kuma lalle Allah Mai tausayi ne, Mai rahama a gare ku.

10. Kuma me ya same ku ne da ba za ku ciyar saboda Allah ba, alhali kuwa gadon sammai da ƙasa na Allah ne? Wanda ya ciyar daga cikinku tun kafin buɗe (Makka) ya kuma yi yaƙi, ba zai zama daidai (da wanda bai

yi) ba. Waɗannan su suka fi girman daraja a kan waɗanda suka ciyar daga bisani, suka kuma yi yaƙi. Amma kuma kowannensu Allah Ya yi masa alƙawarin Aljanna. Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne.

11. Wane ne wanda zai bai wa Allah rance kyakkyawan rance, sai Ya ninka masa shi, alhali yana kuma da lada mai girma?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su yi imani da shi su kuma yi imani da Manzonsa, su kuma ciyar daga dukiyar da ya sanya su masu kula da ita, watau kamar wakilai da ya umarce su su juya ta yadda ya dace da shari'arsa. Sannan ya sanar da su cewa duk waɗanda a cikinsu suka yi imani da shi, suka kuma bayar da dukiyoyinsu saboda shi, to suna da gwaggwaɓan lada a wurinsa, watau gidan Aljanna.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su cewa me ya hana su su yi imani da Allah alhalin ga Manzonsa ya aiko musu yana kiran su zuwa gare shi, don su yi imani da Ubangijinsu (Mai tsarki da ɗaukaka), ga shi kuma ya yi alƙawari da su lokacin da ya fito da su daga tsatson iyayensu cewa za su yi imani, don haka su yi imani mana idan har su muminai ne da gaske.
Wannan shi ne tafisirin Mujahid alamajirin Ibn Abbas, kuma shi ne zaɓin Ibn Jarir.
Ibnu Kasir kuwa yana ganin ma'anar alƙawari da su a nan shi ne mubaya'a da suka yi wa Manzon Allah (ﷺ) cewa za su ji maganarsa su yi masa ɗa'a. Don haka a nan ana nufin tunatar da su wannan alƙawari ne da suka ɗauka, da nuna musu lalle su ci gaba da riƙe shi da bin sa sau-da-ƙafa.
Sai kuma ya bayyana musu wata babbar ni'ima da ya yi musu da cewa, shi ne ya saukar wa Bawansa Muhammadu (ﷺ) ayoyi bayyanannu, domin ya fitar da su daga duffan kafirci da jahilci da son zuciya, zuwa ga hasken imani da ilimi da shiriya. Kuma lalle shi mai tausayi ne da rahama gare su yayin da ya yi musu tagomashin aiko musu da Manzo don ya zama mai kira da shiryarwa a gare su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake nuna musu cewa, ba su da wata hujja da za ta hana su taimaka wa addininsa da dukikoyinsu, domin saninsu ne cewa, duk wata dukiya da suke taƙama da ita tasa ce, domin duk abin da yake sammai da na ƙasa gadonsa ne, watau mallakarsa ne duka, su kawai ajiya ce ya ba su ta ɗan lokaci daga baya za su dawo gare shi baki ɗaya.
Sai kuma ya bayyana musu falalar ciyar da dukiya lokacin tsananin buƙata a kan ciyar da ita lokacin ƙarancin buƙata. Ya tabbatar musu cewa, sahabban da suka yi imani tun farko suka ciyar da dukiyoyinsu suka yi yaƙi tare da Manzonsa (ﷺ) tun kafin a yi Fat'hu Makka, watau a shekara ta takwas, sun fi waɗanda suka yi imani daga bayan Fat'hu Makka suka yi yaƙi tare da Manzon Allah (ﷺ), amma dukkansu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu alƙawarin gidan Aljanna, kuma shi masanin abin da suke aikatawa ne, zai yi wa kowa sakayya gwargwadon aikinsa mai kyau ko mummuna.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake kwaɗaitar da su a kan ciyar da dukiyoyinsu don taimakon Musulunci da Musulmi, ya kira su a kan su ba shi rance mai kyau shi kuma zai ninninka musu sakamako, kuma a ranar alƙiyama suna da wani sakamako mai girma, watau Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ba wa muminai maza da mata haske a lahira, kowannensu gwargwadon imaninsa da ayyukansa nagari da suka gudanar a duniya a cikin hasken ilimi.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ba wa muminai haskensu ta gabansu, watau duk inda za su fuskanta cikin haske za su kasance, da kuma ta damansu, domin ta nan ne za su karɓi littattafan ayyukansu. Saɓanin 'yan wuta waɗanda suke cikin duhu diɗib ba su da wani haske kuma za su karɓi littattafansu ta hagunsu.

3. A ranar alƙiyama za a yi wa munafukai ƙwalele; ta nuna musu hasken da muminai suke ciki, kamar yadda su ma a duniya suka riƙa nuna wa muminai cewa, sun yi imani amma ba da gaske suke ba ƙarya suke. An yi musu sakamako da irin aikinsu kenan.

4. Saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da munafurci su ne suke jawo faɗawa cikin duhu da halaka a ranar alƙiyama.

5. Jiran wata musiba ta faɗa wa muminai da shakka game da tashin alƙiyama da ruɗuwa da Shaiɗan da burace-buracen ƙarya, duk waɗannan siffofi ne na munafukai.

6. Kafiri da munafuki ba su da abin da za su fanshi kansu da shi a ranar alƙiyama.

Suratul Hadid (12-15)
يَوۡمَ تَرَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ يَسۡعَىٰ نُورُهُم بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَبِأَيۡمَٰنِهِم بُشۡرَىٰكُمُ ٱلۡيَوۡمَ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١٢ يَوۡمَ يَقُولُ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتُ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱنظُرُونَا نَقۡتَبِسۡ مِن نُّورِكُمۡ قِيلَ ٱرۡجِعُواْ وَرَآءَكُمۡ فَٱلۡتَمِسُواْ نُورٗاۖ فَضُرِبَ بَيۡنَهُم بِسُورٖ لَّهُۥ بَابُۢ بَاطِنُهُۥ فِيهِ ٱلرَّحۡمَةُ وَظَٰهِرُهُۥ مِن قِبَلِهِ ٱلۡعَذَابُ ١٣ يُنَادُونَهُمۡ أَلَمۡ نَكُن مَّعَكُمۡۖ قَالُواْ بَلَىٰ وَلَٰكِنَّكُمۡ فَتَنتُمۡ أَنفُسَكُمۡ وَتَرَبَّصۡتُمۡ وَٱرۡتَبۡتُمۡ وَغَرَّتۡكُمُ ٱلۡأَمَانِيُّ حَتَّىٰ جَآءَ أَمۡرُ ٱللَّهِ وَغَرَّكُم بِٱللَّهِ ٱلۡغَرُورُ ١٤ فَٱلۡيَوۡمَ لَا يُؤۡخَذُ مِنكُمۡ فِدۡيَةٞ وَلَا مِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۚ مَأۡوَىٰكُمُ ٱلنَّارُۖ هِيَ مَوۡلَىٰكُمۡۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ١٥

12. (Ka tuna) ranar da za ka ga muminai maza da muminai mata haskensu yana tafiya ta gabansu da ta damansu, (ana cewa da su): “Albishirinku a wannan rana (su ne) gidajen Aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, kuna masu dawwama a cikinsu. Wannan shi ne rabo mai girma.”

13. A ranar da munafukai maza da munafukai mata za su riƙa cewa da waɗanda suka yi imani: “Ku saurara mana mu ɗan ɗosani haskenku.” Aka ce (da su): “Ku koma bayanku (watau duniya) sai ku nemi haske.” sai aka raba tsakaninsu da katanga wadda take da wata ƙofa, daga cikinta akwai rahama, bayanta kuma azaba ce (take bugowa) daga gare ta.

14. (Munafukan) suna kiran su cewa: “Yanzu ba mu kasance a tare da ku ba ne?” Suka ce: “Haka ne, sai dai ku kuma kun fitini kanku (da munafunci) kuka kuma saurari (aukuwar mummunan abu ga muminai), kuka kuma yi shakka (game da addini), burace-burace kuma suka ruɗe ku har mutuwa ta zo, Shaiɗan kuma ya ruɗe ku game da Allah.

15. “To a yau ba za a karɓi wata fansa ba daga gare ku da kuma daga waɗanda suka kafirta. Makomarku wuta; ita ce ta kamace ku, makoma kuwa ta munana.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falalar waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari da matsayinsu a ranar alƙiyama ranar da muminai maza da mata za su riƙa tafiya haske ya kewaye su ta gabansu da ta damansu, kowanne gwargwadon imaninsa da kyawawan ayyukansa, ana kuma yi musu albishir a wannan ranar da rabauta da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su shige su kuma su dawwama a cikinsu har abada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa wannan shi ne babban rabo da babu kamarsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon munafukai maza da mata a wannan ranar yayin da za su riƙa roƙon waɗanda suka yi imani cewa, su ɗan saurara musu don su ɗosani wani abu na haskensu wanda zai taimaka musu su tsallake Siraɗi, domin kowannensu ya samu kansa a cikin duhu ƙirin

saboda munanan ayyukansu da suka yi a duniya. To a nan ne za a ba su amsa mai cike da izgili da ban haushi, da cewa su koma can bayansu su nemo haskensu, tare da cewa sun sani ba wani haske da suka bari a baya. Sannan don a ƙara cire musu tsammanin samun biyan wata buƙata tasu sai a sanya shamaki na wata doguwar katanga tsakaninsu da muminai, don su ƙara tabbatar da cewa, abin da suke nema ba zai taba samuwa a gare su ba har abada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta wannan katangar da cewa tana da wata ƙofa daga cikinta, watau ɓangaren muminai rahama ce, bayanta kuma, watau ɓangaren munafukai matsananciyar azaba ce. A nan ne munafukai za su marairaice wa muminai suna yi musu magiya da cewa, ashe ba tare suke a duniya ba, watau su ma ai suna faɗar '*La'ilaha illallahu*' suna kuma yin salla suna yin azumi har ma akan fita jihadi tare da su, amma suka ƙyale su a cikin wannan azabar? Sai muminai su amsa musu da cewa, haka ne suna tare da su a duniya, amma kuma ai ba a nan take ba; akwai bambanci babba a tsakaninsu, domin su sun fitini kansu da munafurci sun hallaka, sannan kuma sun yi sauraron zuwan lokacin da za a cinye muminai da yaƙi don su kuma su fito sarari su bayyana kafircinsu. Hakanan kuma sun yi shakka game da samun nasarar muminai da kuma tashi bayan mutuwa; wannan shi ya jawo burace-buracen ƙarya suka ruɗe su, sai ga shi ba su ankara ba har mutuwa ta zo musu, Shaiɗan kuma ya yi nasara a kansu ya yaudare su da ruɗinsa dangane da sha'anin Allah.Muminai suka bayyana wa munafukai miyagun halayensu na duniya waɗanda suka jawo musu matsanancin halin da suka tsinci kansu a cikinsa a ranar alƙiyama. Suka kuma tabbatar musu cewa, a ranar babu wata fansa da za a karɓa daga wajensu ko daga wajen kafirai waɗanda suka bayyana kafircinsu a fili ballantana har su sami kuɓuta daga azabar Allah, don haka makomarsu su da kafiran sarari ita ce wutar Jahannama, kuma da man ita ce ta fi cancanta da su, to tir da wannan mummunar makoma da suka tsinci kawunansu a ciki.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ambaton Allah da aiki da shari'arsa su ne suke sanya zukata su yi taushi su nutsu.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi muminai da cewa kada su kuskura su kwaikwayi halayen Yahudu da Nasara waɗanda ya saukar musu da littattafai don su yi aiki da su, amma sai suka yi watsi da su suka kama bara-gurbin ra'ayoyin malamansu, suka kuma shigar da bidi'o'i a cikin addininsu, suka mayar da malamansu da waliyyansu ababan bauta ba Allah ba, wanda hakan ya jawo musu ƙeƙashewar zukata suka daina karɓar wa'azi ko tunatarwa gaba ɗaya.

3. Zukata a koyaushe suna buƙatar a riƙa tunatar da su abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar, a kuma riƙa zantar da su maganganu na hikima, idan ba haka ba to za su ƙeƙashe su bushe.

Suratul Hadid (16-17)

*أَلَمۡ يَأۡنِ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن تَخۡشَعَ قُلُوبُهُمۡ لِذِكۡرِ ٱللَّهِ وَمَا نَزَلَ مِنَ ٱلۡحَقِّ وَلَا يَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلُ فَطَالَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَمَدُ فَقَسَتۡ قُلُوبُهُمۡۖ وَكَثِيرٞ مِّنۡهُمۡ فَٰسِقُونَ ١٦ ٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ يُحۡيِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَاۚ قَدۡ بَيَّنَّا لَكُمُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ١٧

16. Yanzu lokaci bai yi ba ga waɗanda suka yi imani zukatansu su yi taushi da zikirin Allah da kuma abin da Ya saukar na gaskiya, kuma kada su zama kamar waɗanda aka bai wa Littafi tun gabaninsu, sai lokaci ya tsawaita a gare su, sai zukatansu suka ƙeƙashe; mafiya yawa kuma daga cikinsu fasiƙai ne?

17. Ku sani cewa Allah Yana raya ƙasa bayan mutuwarta. Haƙiƙa Mun bayyana muku ayoyi don ku hankalta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin muminai da tsawatar musu game da sakaci wajen ambaton sa, da cewa, ashe lokaci bai yi ba da ya kamata zukatansu su yi taushi su nutsu da ambaton

Allah da ayoyin Alƙur’ani da suka sauka masu ɗauke da kyakkyawan alƙawari ko narkon azaba, kada kuma su yarda su zama kamar Yahudawa da aka ba wa littafin Attaura ko Nasara da aka ba wa littafin Linjila aka umarce su da yin aiki da su, amma kuma bayan ɗaukar tsawon lokaci da rabuwa da annabawansu sai suka yi watsi da waɗannan littattafai suka manta da ambaton Allah da shari’arsa, har zukatansu suka ƙeƙashe, yawancinsu suka wayi gari sun zama fasiƙai masu saba wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka)?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu yadda sauraron wa’azi da karatun Alƙur’ani yake yin tasiri a zukata kamar yadda ruwan sama yake yin tasiri idan ya sauka a kan ƙeƙasasshiyar ƙasa, yake raya ta bayan ta mutu. To hakanan Alƙur’ani yake raya zukata bayan sun ƙeƙashe. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, yana bayyana musu ayoyinsa ne masu nuna cikar Kudurarsa da Kaɗaitakarsa don mutane su hankalta su ɗauki izina da darasi daga gare su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gwaggwaɓan ladan masu sadaka da dukiyarsu don Allah.

2. Girman ihsanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da rahamarsa ga bayinsa yayin da za su yi kyakkyawan aiki ɗaya amma sai ya ninninka musu ladansu ninki mai yawa.

3. Waɗannan ayoyi sun ƙunshi kashe-kashen mutane huɗu:
Na farko, masu yawan sadaka, su ne masu yawan kyautata wa bayin Allah da amfanar da su iya ƙokarinsu, musamman da dukiyarsu, don Allah.
Na biyu, siddiƙai, su ne waɗanda suka cika matakan imani da aiki na ƙwarai da ilimi mai amfani tare da yaƙini mai zurfi.
Na uku, su ne shahidai waɗanda aka kashe su wajen ɗaukaka kalmar Allah.
Na huɗu, su ne kafirai ‘yan wuta waɗanda suka ƙaryata Allah da Manzonsa da ayoyinsa.

Suratul Hadid (18-19)

إِنَّ ٱلْمُصَّدِّقِينَ وَٱلْمُصَّدِّقَٰتِ وَأَقْرَضُوا۟ ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا يُضَٰعَفُ لَهُمْ وَلَهُمْ أَجْرٌ كَرِيمٌ ﴿١٨﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦٓ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصِّدِّيقُونَ ۖ وَٱلشُّهَدَآءُ عِندَ رَبِّهِمْ لَهُمْ أَجْرُهُمْ وَنُورُهُمْ ۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَكَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَآ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَحِيمِ ﴿١٩﴾

18. Lalle masu yin sadaka maza da masu yin sadaka mata, suka kuma bai wa Allah kyakkyawan rance, to za a ninninka musu shi, suna kuma da wani ladan mai daraja.

19. Waɗanda kuma suka yi imani da Allah da manzanninsa, waɗannan su ne siddiƙai; shahidai kuma suna da ladansu da haskensu a wurin Ubangijinsu; waɗanda kuwa suka kafirta suke kuma ƙaryata ayoyinmu, to waɗannan su ne ‘yan (wutar) Jahimu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana falalar maza da mata masu yawan sadaka da dukiyoyinsu don Allah don taimakon addininsu da ‘yan’uwansu muminai, suka kuma ba wa Allah kyakkyawan rance, to Allah zai ninninka musu ladansu, kowanne kyakkyawan aiki ɗaya za a ninka shi goma irinsa, har zuwa ɗari bakwai, har zuwa ninkin da ba adadi, tare da haka kuma suna da wani lada na karamci a wurin Allah, watau gidan Aljanna.Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa gaba ɗayansu, to waɗannan su ne siddiƙai a wurin Allah, watau matsayinsu shi ne yake biye da matsayin annabawa. Su kuma shahidai, watau waɗanda suka yi mutuwar shahada wajen ɗaukaka kalmar Allah, to suna da ladansu na karramawa da Ubangijinsu ya tanadar musu,

suna da kuma haskensu wanda zai riƙa tafiya ta gabansu da ta damansu a ranar alƙiyama. Waɗanda kuma suka kafirce wa Allah da Manzonsa, suka kuma ƙaryata ayoyin da ya saukar wa Manzonsa, to waɗannan su ne ‘yan wuta waɗanda za su shige ta ranar alƙiyama su kuma dawwama a cikinta har abada babu ranar fita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi a kan guje wa duniya da ƙyale-ƙyalenta, domin ba ta da tabbas, tare da himmatuwa a kan sha’anin lahira, domin ita ce rayuwa ta haƙiƙa wadda ba ta yankewa.

2. Halin duniya da masu ruɗuwa da ita waɗanda take ɗauke wa hankali da wasanninta da sharholiyarta, sai su dawo babu abin da yake gabansu sai fariya da gasa wajen tara dukiya da ‘ya’ya da neman matsayi, su manta da neman yardar Allah da gyara lahirarsu, daga ƙarshe sai su wayi gari ba duniyar ba kuma lahirar sai azaba mai tsanani.

3. Kwaɗaitarwa game da rige-rige wajen ayyukan alheri da yawan tuba da istigfari da guje wa ayyukan saɓon Allah da rungumar ayyuka nagari da ƙoƙarin neman yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta hanyar bautar sa da kyautata wa bayinsa.

4. Aljannar Allah falalarsa ce mai girma ga bayinsa muminai.

Suratul Hadid (20-21)
ٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا لَعِبٞ وَلَهۡوٞ وَزِينَةٞ وَتَفَاخُرُۢ بَيۡنَكُمۡ وَتَكَاثُرٞ فِي ٱلۡأَمۡوَٰلِ وَٱلۡأَوۡلَٰدِۖ كَمَثَلِ غَيۡثٍ أَعۡجَبَ ٱلۡكُفَّارَ نَبَاتُهُۥ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَىٰهُ مُصۡفَرّٗا ثُمَّ يَكُونُ حُطَٰمٗاۖ وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِ عَذَابٞ شَدِيدٞ وَمَغۡفِرَةٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضۡوَٰنٞۚ وَمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَآ إِلَّا مَتَٰعُ ٱلۡغُرُورِ ٢٠ سَابِقُوٓاْ إِلَىٰ مَغۡفِرَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ وَجَنَّةٍ عَرۡضُهَا كَعَرۡضِ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ أُعِدَّتۡ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦۚ ذَٰلِكَ فَضۡلُ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٢١

20. Ku sani cewa, ita dai rayuwar duniya ba wata aba ba ce sai wasa da sharholiya da ƙyale-ƙyale da kuma fariya a tsakaninku da takara wajan nuna yawan dukiya da ‘ya’yaye; ta yi kama da ruwan saman da tsirransa suka bai wa manoma sha’awa, sannan duk ya bushe, sai ka gan shi fatsi-fatsi, sannan kuma ya zama dudduga; a lahira kuwa akwai azaba mai tsanani da gafara daga Allah da kuma yarda. Rayuwar duniya ba komai ba ce sai jin daɗi mai ruɗi.

21. Ku yi rige-rige zuwa neman gafara daga Ubangijinku da Aljanna wadda faɗinta kamar faɗin sammai da ƙasa yake, an tanade ta don waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa. Wannan falalar Allah ce da Yake ba da ita ga wanda Ya ga dama. Allah kuwa Ma’abocin falala ne, Mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana matsayin duniya ne da rayuwar mutanenta, inda ya nuna cewa, abin da yake cikinta bai wuce wasa da sharholiya ba waɗanda suke ɗauke hankalin mutum daga tunanin wani abu mai muhimmanci a rayuwarsa, kuma ado ce da mutanen cikinta suke kwalliya da ita, suke fama wajen ƙawata tufafinsu da abincinsu da abin shansu da ababan hawansu da gidajensu; kuma abar fariya ce a tsakanin mutanen cikinta wajen nuna isa da mulki da matsayi da jin daɗi; kuma takara ce a tsakaninsu wajen tara dukiya da ‘ya’ya. Waɗannan kuwa duk wasu abubuwa ne masu saurin ƙarewa, a wayi gari kamar ba a taɓa ganin su ba. Wannan ya yi kama da ruwan sama mamako da ya sauko ya mayar da ƙasa koriya shar da shuke-shukenta har tsirranta suka riƙa ba manoma sha’awa, to

amma bayan ɗan lokaci ƙanƙani sai ga shi tsirran sun bushe sun yi fatsi-fatsi, sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da su dudduga, duk kyansu ya gushe amfaninsu ya ƙare. To haka rayuwar duniya take, sai bayan ta haska wa mai neman ta ya hango ƙyale-ƙyalenta, ta buɗe masa ƙofofinta yana samun biyan buƙatunsu daga gare ta, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gusar da ita daga hannunsa ya aiko masa mutuwa ta ɗauke shi daga cikinta ɗungurungum ba abin da zai tsira da shi sai ƙyallen likkafani, don haka mene ne amfanin raja'a a kanta a manta da lahira wadda ta ƙunshi yanayi biyu kacal a cikinta ga duk wani ɗan'adam; ko dai azaba mai tsanani ta wutar Jahannama ga waɗanda suka kafirta ko suka zaɓi rayuwar munafurci, ko kuma gafarar zunubai daga Allah ga bayinsa muminai da samun yardarsa a gidan Aljanna. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, rayuwar duniya ba komai ba ce sai ɗan jin daɗi mai ruɗi wanda ba ya ɗorewa, don haka duk wanda ya zaɓi rayuwar duniya a kan ta lahira to wannan shi ne ya yi asara ya taɓe har abada.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mutane da yin rige-rige zuwa ga ayyuka na ƙwarai waɗanda da su ne za su sami gafarar zunubansu, sannan su samu Aljanna wadda faɗinta kamar faɗin sama da ƙasa ne, kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanade ta ne ga waɗanda suka yi imani da Allah da manzanninsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan falalarsa ce da yake bayar da ita ga wanda ya ga dama daga bayinsa kuma shi ma'abocin falala mai girma ne ga bayinsa muminai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin yin imani da ƙaddara.

2. Imani da ƙaddara ya ƙunshi tabbatar da cewa, komai da zai faru a sama ko a ƙasa mai daɗi ko marar daɗi tuni Allah ya riga ya rubuta shi a cikin Lauhul Mahfuzu.
3. Hikimar yin imani da ƙaddara shi ne cire wa bawa damuwa game da duk abin da ya rasa ko fariya da taƙama da abin da ya samu, domin duka yin Allah ne, kuma a rubuce yake a wurinsa babu makawa sai ya faru.

4. Haramcin nuna girman kai da taƙama ga mutane.

5. Haramcin rowa da muninta.

6. Mafi munin marowaci shi ne wanda bai taƙaita yin rowar a kansa shi kaɗai ba, har sai da ya riƙa umartar mutane da yin ta.

7. Duk wani mai mummunan aiki yana so ya samu abokan tarayya da shi cikin wannan mummunan aikin.

8. Kauce wa hanyar Allah da karantarwar manzanninsa shi ne yake jawo tsananin rowa da hana haƙƙin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

9. Cikar wadatar Allah da rashin buƙatuwarsa ga wata ibada ta bayinsa.

Suratul Hadid (22-24)
مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِيٓ أَنفُسِكُمۡ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مِّن قَبۡلِ أَن نَّبۡرَأَهَآۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٢٢ لِّكَيۡلَا تَأۡسَوۡاْ عَلَىٰ مَا فَاتَكُمۡ وَلَا تَفۡرَحُواْ بِمَآ ءَاتَىٰكُمۡۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخۡتَالٖ فَخُورٍ ٢٣ ٱلَّذِينَ يَبۡخَلُونَ وَيَأۡمُرُونَ ٱلنَّاسَ بِٱلۡبُخۡلِۗ وَمَن يَتَوَلَّ فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡغَنِيُّ ٱلۡحَمِيدُ ٢٤

22. Babu wani abu da ya samu na musiba a bayan ƙasa, ko kuma ga kawunanku face yana cikin Littafin (Lauhul Mahafuzu) tun kafin Mu halicce ta (watau halittar). Lalle wannan (a wurin Allah) mai sauƙi ne.

23. Don kada ku yi baƙin ciki a kan abin da ya kuɓuce muku, kada kuma ku yi fariya da abin da Ya ba ku, Allah kuwa ba Ya son duk wani mai taƙama, mai fariya.

24. (Su ne) waɗanda suke yin rowa, suke kuma umartar mutane da yin rowar. Wanda kuwa ya ba da baya, to lalle Allah Shi Mawadaci ne, Sha-Yabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, kowane abu yana gudana ne bisa ƙaddararsa mai daɗi ne ko marar daɗi. Ya tabbatar da cewa, babu wata musiba da za ta samu mutane a bayan ƙasa, kamar fari, ko ta same su a kawunansu, kamar annobar rashin lafiya ko mace-mace, face wannan abu yana nan a rubuce tun farko a cikin Littafin Lauhul Mahfuzu tun ma kafin ya halicci halittu, kuma yin haka aiki ne mai sauƙi a wurinsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Allah ya rubuta abubuwan da ya ƙaddara wa halittunsa tun kafin ya halicci sammai da ƙasa da shekara dubu hamsin. Al’arshinsa kuma yana kan ruwa.” [Muslim #2653 da Ahmad #6579].

Kuma Allah ya bayyana cewa, ya yi haka ne saboda wata hikima, ita ce mutane su gane wannan ƙa’idar tasa, su gina komai nasu a kanta, su ɗora duk wani abu na alheri ko na sharri a kan ma’auninta, don haka ba za su yi baƙin ciki game da abin da ya kuɓuce musu ba, ba kuma za su riƙa fariya da girman kai a kan abin da Allah ya ga dama ya ba su ba, domin ba ya son duk wani mai girman kai mai nuna taƙama da fariya a kan wata ni’ima ta duniya da Allah ya ba shi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon waɗanda suke yin rowa ba sa bayar da haƙƙoƙin Allah daga dukiyar da ya ba su, har ma suna zuga mutane kan su yi rowar abin da yake hannunsu; ya tabbatar da cewa, waɗannan su ne asararru, domin duk wanda ya bijire wa ɗa’ar Allah ya juya wa umarninsa baya, to ba zai cutar da Allah da komai ba, sai dai kansa kawai ya cutar, domin Allah mai cikakkiyar wadata ne ba ya da buƙatar ɗa’ar bayinsa, kuma shi sha-yabo ne a kowanne hali.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa, yayin da ya aiko musu da manzanni ya saukar musu da littattafai masu ƙunshe da cikakkun bayanai game da Allah abin bautarsu da kuma hanyar bauta masa.

2. Gaskiya dole ne tana buƙatar ƙarfi da zai ba ta kariya, wannan ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da baƙin ƙarfe wanda ake ƙera makaman yaƙi da shi, don ba wa gaskiya kariya a koyaushe.

3. Mutane iri biyu ne, wani yakan miƙa wuya da zarar ya ga hujjoji bayyanannu ya saurari wa’azi; wani kuma babu abin da yake sanya shi ya rusuna ya miƙa wuya sai ya ga an fi ƙarfinsa, don haka sai Allah ya haɗo manzanninsu da duka hanyoyin guda biyu.

4. Adalci da doka koyaushe suna buƙatar ƙarfi da zai ba su kafiya; don haka kowace daula dole ne ta samar da ɓangaren shari’a da kuma ɓangaren tsaro.

5. Duk wata shari’a da Allah ya aiko manzanninsa da ita ta zo ne don tabbatar da cikakken adalci ga ɗan’adam, don haka kauce wa shari’ar Allah kauce wa adalci ne a bayan ƙasa.

Suratul Hadid (25)

لَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا رُسُلَنَا بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَأَنزَلۡنَا مَعَهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡمِيزَانَ لِيَقُومَ ٱلنَّاسُ بِٱلۡقِسۡطِۖ وَأَنزَلۡنَا ٱلۡحَدِيدَ فِيهِ بَأۡسٞ شَدِيدٞ وَمَنَٰفِعُ لِلنَّاسِ وَلِيَعۡلَمَ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥ وَرُسُلَهُۥ بِٱلۡغَيۡبِۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِيٌّ عَزِيزٞ ٢٥

25. Haƙiƙa Mun aiko manzanninmu da (ayoyi) mabayyana, Muka kuma saukar da littafi da ma’auni a tare da su (manzannin) don mutane su tsaya da adalci; Muka kuma saukar da baƙin ƙarfe wanda a tare da shi akwai tsananin ƙarfi da kuma amfani ga mutane, don kuma Allah Ya bayyanar da wanda yake taimakon Sa da manzanninsa a ɓoye. Lalle Allah Mai ƙarfi ne, Mabuwayi.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya aiko manzanninsa da hujjoji bayyanannu, ya kuma saukar musu da littattafai waɗanda suka ƙunshi shiriya da shari’a, ya kuma saukar musu da ma’auni don mutane su tsayar da adalci a tsakaninsu, a cikin maganganunsu da ayyukansu da mu’amalolinsu. Ya kuma saukar da baƙin ƙarfe wanda yake akwai tsananin ƙarfi tare da shi, domin da shi mutane suke yin makaman yaƙi, suke kuma amfani da shi a sauran sana’o’insu da ƙere-ƙerensu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi haka ne don ya bayyana wanda yake taimakon sa shi da manzanninsa a ɓoye, sai ya bayyana shi kowa ya gan shi. Lalle Allah mai ƙarfi ne mabuwayi, babu mai iya karawa da shi ya kai labari.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk annabawa sun fito ne daga zurriyar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Dangantaka da mutanen kirki kaɗai ba za ta amfanar da mutum ba matuƙar bai yi imani ba.

3. Haramcin shigo da bidi’a a cikin addini, yin haka kuma koyi ne da malaman Nasara.

4. Taryar wahala da gangan da sunan addini ko bautar Allah, ba ya daga cikin addinin Allah. Wannan wani salo ne da Nasara suka ƙirƙira da sunan bautar Allah a cikin addininsu, yayin da ɗayansu zai fita daga cikin jama’a ya kebance kansa a wani wuri nesa da mutane wai shi yana bautar Allah, ya ƙaurace wa duk wani al’amari na rayuwar duniya, kamar yin aure ko kasuwanci ko shugabanci. Sukan tare a jeji ne su gina wa kawunansu tsangaya don gudun gaurayuwa da jama’a. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya soke su a kan haka bai yaba musu ba.

Suratul Hadid (26-27)

وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحٗا وَإِبۡرَٰهِيمَ وَجَعَلۡنَا فِي ذُرِّيَّتِهِمَا ٱلنُّبُوَّةَ وَٱلۡكِتَٰبَۖ فَمِنۡهُم مُّهۡتَدٖۖ وَكَثِيرٞ مِّنۡهُمۡ فَٰسِقُونَ ٢٦ ثُمَّ قَفَّيۡنَا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم بِرُسُلِنَا وَقَفَّيۡنَا بِعِيسَى ٱبۡنِ مَرۡيَمَ وَءَاتَيۡنَٰهُ ٱلۡإِنجِيلَۖ وَجَعَلۡنَا فِي قُلُوبِ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ رَأۡفَةٗ وَرَحۡمَةٗۚ وَرَهۡبَانِيَّةً ٱبۡتَدَعُوهَا مَا كَتَبۡنَٰهَا عَلَيۡهِمۡ إِلَّا ٱبۡتِغَآءَ رِضۡوَٰنِ ٱللَّهِ فَمَا رَعَوۡهَا حَقَّ رِعَايَتِهَاۖ فَـَٔاتَيۡنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنۡهُمۡ أَجۡرَهُمۡۖ وَكَثِيرٞ مِّنۡهُمۡ فَٰسِقُونَ ٢٧

26. Haƙiƙa kuma Mun aiko Nuhu da Ibrahimu, Muka kuma sanya annabta da littafi cikin zuriyarsu; To daga cikinsu akwai shiryayyu, masu yawa kuwa daga cikinsu fasiƙai ne.

27. Sannan a bayansu Muka biyar da manzanninmu, Muka kuma biyar da Isa ɗan Maryamu Muka kuma ba shi Linjila, kuma Muka sanya jin ƙai da rahama a cikin zukatan waɗanda suka bi shi. Rahbaniyanci kuma su ne suka ƙago shi, ba Mu wajabta musu shi ba, sai dai (Mun wajabta musu) neman yardar Allah, amma

ba su kiyaye shi ba kamar yadda ya kamata; sai Muka bai wa waɗanda suka yi imani daga cikinsu ladansu; da yawa kuwa fasiƙai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wasu manyan annabawansa waɗanda ya aiko ya kuma sanya sauran annabawansa suka fito daga zurriyarsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya aiko Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda shi ne farkon manzannin Allah a bayan ƙasa, ya kuma aiko Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) uban annabawa. Waɗannan manzanni biyu ya zaɓe su ya kuma sanya annabci a cikin zurriyarsu, watau yawancin annabawan da suka zo duniya daga tsatsonsu suka fito. Hakanan kuma ya saukar musu da littattafai. To daga cikin zurriyar waɗannan annabawan biyu akwai wanda yake shiryayye ne yana bin tafarkin Allah miƙaƙƙe, amma kuma da dama daga cikinsu fasiƙai ne masu kauce wa hanya madaidaiciya.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya ci gaba da aiko manzanninsa ɗaya bayan ɗaya zuwa ga al'ummunsu suna yi musu wa'azi, har ya aiko da Annabi Isa ɗan Maryam (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a bayansu, shi ma ya ba shi littafin Linjila, ya kuma haɗa shi da mabiya waɗanda suka yi imani da shi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sanya jin tausayi da rahama a cikin zukatansu, suka zamanto masoya juna, masu tausayin juna, amma kuma daga baya sai suka ƙagi bidi'ar Rahbaniyanci a addininsu, suka ƙaurace wa aure da cin daɗaɗan abubuwa na halal, suka haramta wa kawunansu wasu abubuwa da Allah ya halatta musu, tare da cewa ba Allah ne ya nemi hakan daga gare su ba; su ne kawai suka lazimta wa kawunansu yin bidi'a a cikin addininsu. Abin da kawai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗora musu shi ne neman yardarsa ta hanyar riƙo da shari'arsa amma sai suka yi watsi da haka. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bai wa waɗanda suka yi imani daga cikinsu ladansu cikakke, amma yawancinsu fasiƙai ne, domin sun bijire wa ɗa'ar Allah sun kuma ƙaryata abin da Annabi Muhammadu (ﷺ) ya zo da shi na Musulunci.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar *Ahlulkitabi* waɗanda suka yi imani da Annabi (ﷺ).

2. Duk wani daga cikin ma'abota littafi, Yahudu da Nasara da ya riski Manzon Allah (ﷺ) bai yi imani da shi ba, to imaninsa da sauran manzannin Allah ba zai amfanar da shi komai ba.

3. Falala ta Allah ce a hannunsa take, shi ne mai bayar da ita ga wanda ya ga dama, don haka a wurinsa ake neman ta a samu.

Suratul Hadid (28-29)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَءَامِنُواْ بِرَسُولِهِۦ يُؤۡتِكُمۡ كِفۡلَيۡنِ مِن رَّحۡمَتِهِۦ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ نُورٗا تَمۡشُونَ بِهِۦ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٨ لِّئَلَّا يَعۡلَمَ أَهۡلُ ٱلۡكِتَٰبِ أَلَّا يَقۡدِرُونَ عَلَىٰ شَيۡءٖ مِّن فَضۡلِ ٱللَّهِ وَأَنَّ ٱلۡفَضۡلَ بِيَدِ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٢٩

28. Ya ku waɗanda suka imani, ku kiyaye dokokin Allah, ku kuma yi imani da Manzonsa, zai ba ku riɓi biyu na rahamarsa, Ya kuma sanya muku haske da za ku riƙa tafiya da shi, kuma Ya gafarta muku. Domin kuwa Allah Mai gafara ne, Mai rahama.

29. Don ma'abota littafi su san cewa ba su da hannu a falalar Allah, don ko lalle falala a hannun Allah take, Yana ba da ita ga wanda Ya ga dama. Allah kuma Ma'abocin babbar falala ne.

A waɗannan ayoyi na ƙarshen Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin muminai waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma yi aiki da shari'arsa, da cewa su kiyaye dokokinsa, su aikata umarninsa, su guji haninsa, su kuma yi imani da Manzonsa (ﷺ); idan sun yi haka zai ninka ladansu kashi biyu; na farko na imaninsu da Annabi (ﷺ), na biyu kuma na imaninsu da manzannin da suka gabata. Sannan kuma zai ba su wani haske wanda zai haskaka musu hanyarsu a duniya su tafi bisa tafarki madaidaici, ya kuma haska musu Siraɗi a ranar alƙiyama, sannan kuma ya gafarta musu zunubbansu ya rufa musu asirinsu a lahira, domin shi mai yawan gafarta zunuban bayinsa ne, mai rahama gare su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ya bayyana wa mutane girman falalarsa da sakamakon da ya tanadar wa muminai riɓi biyu ko ma fiye da haka, don Yahudawa da Nasara su fahimci cewa falalar Allah ba a hannunsu take ba balle su ce za su ba wanda suka ga dama, su hana wanda suka ga dama; falala ta Allah ce, a hannunsa take, yana bayar da ita ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, domin shi ne ma'abocin babbar falala, mai yin yadda ya ga dama da ita.

An karɓo daga Abu Musa (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mutum uku ana ba su ladansu sau biyu; mutumin da ya yi imani da littafin farko ya kuma yi imani da littafin ƙarshe; da mutumin da yake da baiwa ya yi mata tarbiyya ya kuma kyautata tarbiyyarta, sannan ya 'yanta ta ya aure ta; da bawa abin mallaka wanda ya kyautata bautar Ubangijinsa, ya kuma kyautata wa mai gidansa." [Bukhari #3011 da Muslim #154].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Luɗufin Allah ga bayinsa masu rauni da taimakonsa a gare su ta yadda yake karɓa musu addu'o'insu ya biya musu buƙatunsu.

2. Samun hanyoyi daban-daban na kaffara yana daga cikin rahamar Allah ga bayinsa da sauƙin da ke cikin shari'arsa.

3. Yin zihari ga mataye al'ada ce ta kafirai, don haka ya wajaba a kan muminai su guje ta domin aikata ta haramun ne.

4. Bayanin yalwar jin Allah da kewayewar iliminsa ga komai.

5. Maganar fatar baki ba ta canza abubuwa daga yadda suke a wurin Allah. Matar mutum ba za ta taɓa zama haramun a wurinsa kamar mahaifiyarsa ba, don kawai ya furta haka da fatar bakinsa, domin mahaifiyarsa ita ce wadda ta tsuguna ta haife shi

58-Suratul Mujadila

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da '*Suratul Mujadila*' ko '*Suratul Majadala*'. '*Mujadila*' tana nufin mace mai jayayya ko muhawara. '*Mujadala*' kuwa tana nufin jayayya ko muhawara tsakanin mutum biyu. An ambaci wannan Sura da wannan suna ne saboda ta buɗe da labarin matar da ta zo wurin Annabi (ﷺ) tana muhawara da shi game da mijinta wanda ya yi mata zihari, kamar yadda bayani zai zo nan gaba da yardar Allah.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malam Ibnu Aɗiyya ya ce, malamai sun haɗu a kan cewa Sura ce *Madaniyya*.

3. Jerin Saukarta
Ita ce Sura ta ɗari da uku (103) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Munafiƙun*' kafin '*Suratut Tahrim*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin da biyu ne (22) a lissafin mutanen Sham da Basra da Kufa. Amma a lissafin mutanen Madina da Makka adadinsu ashirin da ɗaya ne (21).

5. Babban Jigonta:
Tana karantar da Musulmi cewa ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kewaye komai, yana kuma ji yana ganin kowa, don haka dole ne a koyaushe su kasance masu tsoron sa masu kiyaye dokokinsa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Hukunci a kan lamarin Ausu ɗan Samitu wanda ya yi wa matarsa Khaulatu 'yar Sa'alaba zihari.
• Rushe al'adar Larabawa ta zamanin jahiliyya ta haramta mace ga mijinta wanda ya yi mata zihari da siffanta wannan zihari a matsayin ƙarya da maganar banza wadda ta saba wa shari'ar Allah.
• Bayanin wasu miyagun halayen munafukai kamar tattaunawa a keɓe don baƙanta wa muminai rai da ƙulla ƙawance da Yahudawa da rantsuwa a kan ƙarya.
• Bayani a kan wasu ladubban majalisar Manzon Allah (ﷺ).
• Yaba wa muminai game da yadda suke nesanta kansu daga Yahudawa da mushirikai da tabbatar musu da cewa su ne rundunar Allah da Manzonsa, kuma su ne masu rinjaye.

Suratul Mujadila (1-4)
قَدْ سَمِعَ ٱللَّهُ قَوْلَ ٱلَّتِى تُجَـٰدِلُكَ فِى زَوْجِهَا وَتَشْتَكِىٓ إِلَى ٱللَّهِ وَٱللَّهُ يَسْمَعُ تَحَاوُرَكُمَآ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ بَصِيرٌ ۝١ ٱلَّذِينَ يُظَـٰهِرُونَ مِنكُم مِّن نِّسَآئِهِم مَّا هُنَّ أُمَّهَـٰتِهِمْ ۖ إِنْ أُمَّهَـٰتُهُمْ إِلَّا ٱلَّـٰٓـِٔى وَلَدْنَهُمْ ۚ وَإِنَّهُمْ لَيَقُولُونَ مُنكَرًا مِّنَ ٱلْقَوْلِ وَزُورًا ۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَعَفُوٌّ غَفُورٌ ۝٢ وَٱلَّذِينَ يُظَـٰهِرُونَ مِن نِّسَآئِهِمْ ثُمَّ يَعُودُونَ لِمَا قَالُوا۟ فَتَحْرِيرُ رَقَبَةٍ مِّن قَبْلِ أَن يَتَمَآسَّا ۚ ذَٰلِكُمْ تُوعَظُونَ بِهِۦ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ۝٣ فَمَن لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ

شَهۡرَيۡنِ مُتَتَابِعَيۡنِ مِن قَبۡلِ أَن يَتَمَآسَّاۖ فَمَن لَّمۡ يَسۡتَطِعۡ فَإِطۡعَامُ سِتِّينَ مِسۡكِينٗاۚ ذَٰلِكَ لِتُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۚ وَتِلۡكَ حُدُودُ ٱللَّهِۗ وَلِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٌ أَلِيمٌ ۝٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Haƙiƙa Allah ya ji zancen wadda take muhawara da kai game da (lamarin) mijinta, tana kuma kai ƙara zuwa ga Allah, Allah kuma Yana jin muhawararku. Lalle Allah Mai ji ne, Mai gani.

2. Waɗanda suke yin zihari daga cikinku ga matansu, su ba iyayensu mata ba ne; iyayensu mata su ne waɗanda kawai suka haife su. Lalle kuma su tabbas suna faɗar muguwar magana ne da tsagwaron ƙarya. Kuma lalle Allah tabbas Mai afuwa ne, Mai gafara.

3. Waɗanda kuwa suke yin zihari ga matansu sannan suka yi niyyar janye abin da suka faɗa, to sai su ‘yanta wuyaye (bawa namiji ko mace), tun kafin su sadu. Wannan (shi ne abin da) ake yi muku wa’azi da shi. Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne.

4. Sannan wanda bai samu ba, to sai ya yi azumin wata biyu a jere tun kafin su sadu; sannan wanda bai sami iko ba sai ya ciyar da miskini sittin. Wannan kuwa don ku yi imani da Allah da Manzonsa. Waɗannan kuma su ne iyakokin Allah. Kafirai kuma suna da azaba mai raɗaɗi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da labarin wata mace mai suna Khaulatu ‘yar Sa’alaba wadda mijinta ya kwatanta ta da mahaifiyarsa, watau ya ce mata: “Ke a wurina kamar bayan mahaifiyata ne.” A zamanin jahiliyya idan mutum ya faɗa wa matarsa irin wannan maganar, to ta haramta a gare shi har abada. Sai Khaulatu ta kawo kukanta wurin Manzon Allah (ﷺ) game da abin da mijinta Ausu ɗan Samit ya yi mata, bayan ga shi ta tsufa suna kuma da ‘ya’ya a tsakaninsu, don haka tana neman ta ji hukuncin Allah a kai, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyi yana tabbatar wa da Manzonsa (ﷺ) cewa lalle ya ji maganar matar nan da take muhawara da shi game da lamarin mijinta Ausu wanda ya yi mata zihari, tana kai kukanta zuwa ga Allah, kuma Allah yana jin muhawararsu da tattaunawarsu, domin yana jin dukkan maganganun bayinsa, yana kuma ganin dukkan ayyukansu, babu abin da yake ɓuya gare shi.

An karɓo daga A’isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: “Yabo da godiya sun tabbata ga wanda jinsa ya yalwaci dukkan sautuka. Matar nan mai jayayya ta zo wa Annabi (ﷺ) tana yi masa magana, ni kuma ina wani ɓangare na wannan gida amma ba na jin abin da take faɗa, sai ga shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: “Haƙiƙa Allah ya ji zancen wadda take jayayya da kai game da lamarin mijinta....” har zuwa ƙarshen aya.” [Ahmad #24195 da Nasa’i #3460 da Ibni Maja #188].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mazajen da suka yi zihari ga matayensu har ɗayansu ya ce wa matarsa: “Ke a wurina kamar bayan mahaifiyata ne”, wannan maganar ƙarya ce, domin matayensu ba iyayensu ne ba, iyayensu su ne kawai waɗanda suka tsuguna suka haife su, kuma wannan maganar da suke faɗa mummunar magana ce kuma ƙarya ce tsagwaranta suke shararawa. Don haka masu irin wannan magana su gaggauta tuba zuwa ga Allah, lalle Allah mai afuwa ne mai gafara, don haka ne ma ya shar’anta musu yadda za su yi kaffara don su tsarkake kawunansu daga zunubi.
Sannan Allah ya bayyana musu hanayar kaffarar warware abin da suka yi na zihari, watau shi ne su sani cewa bai halatta su koma zuwa ga saduwa da matansu ba har sai sun ‘yanta bawa ko baiwa. Allah ya bayyana cewa, an umarce su ne da wannan hukunci don ya zama tsawatarwa a gare su game da aikata zihari nan gaba, kuma Allah masanin abin da suke aikatawa ne, babu wani aikinsu da bai sani ba.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, wanda bai samu baiwa ko bawan da zai ‘yanta ba, to sai ya yi azumin wata biyu a jere kafin ya koma ga saduwa da matarsa da ya yi wa zihari. Wanda kuma ya kasa yin azumin, to sai ya ciyar da miskini sittin. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu wannan hukunci ne don su yi imani da cewa Allah ne ya shar’anta musu shi, don haka dole ne su bi umarninsa, su kuma sani cewa duk waɗannan hukunce-hukunce iyakokin Allah ne da ya shata wa bayinsa, ya kuma hana su tsallake su, duk kuma waɗanda suka kafirce wa dokokinsa da hukunce-hukuncensa suna da azaba mai raɗaɗi.An karɓo daga Khaulatu ‘yar Sa’alaba, (Allah ya ƙara mata yarda), ta ce: “Wallahi a kaina, ni da mijina Ausu ɗan Samit Allah ya saukar da ayoyin farko na ‘*Suratul* Mujadila’.” Ta ce: “Na kasance a ƙarƙashinsa, shi kuma ya kasance tsoho mai shekaru har rikicin tsufa ya kama shi; sai wata rana ya shigo gida, sai ya yi wata magana ni kuma na yi masa musu, sai ya yi fushi ya ce mini: “Ke a wurina kamar bayan mahaifiyata kike.” Sai ya fita ya je majalisar abokansa sannan ya dawo gida yana son in amince da shi, ni kuwa na ce sam ba zan amince da shi ba, na rantse masa da cewa hannunsa ba zai ƙara taɓa jikina ba bayan ya faɗi maganar da ya faɗa har sai Allah da Manzonsa (ﷺ) sun yi hukunci a tsakaninmu. Sai na je na samu Manzon Allah na kwashe labarin abin da ya faru tsakanina da mijina na gaya masa. Ban bar wajensa ba har sai da Alƙur’ani ya sauko. Gumi da yake lulluɓe Manzon Allah idan za a yi masa wahayi sai ya lulluɓe shi. Sannan da aka yaye masa, sai ya ce mini: “Ya ke Khaulatu, lalle Allah ya saukar da ayoyin Alƙur’ani game da ke da mutuminki.” Sai ya karanta mini ayoyi huɗu na farkon Surar, sai ya ce mini: “Ki umarce shi ya ‘yanta wuyaye.” (Watau bawa ko baiwa). Sai na ce: “Ya Manzon Allah ba ya da abin da zai ‘yanta.” Sai ya ce: “To ya yi azumin wata biyu a jere.” Sai na ce: “Wallahi ya tsufa tukuf ba zai iya yin azumi ba.” Sai ya ce: “To ya ciyar da miskini sittin sa’i sittin na dabino.” Sai na ce: “Wallahi ba ya da shi.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “To mu za mu taimaka masa da kwandon dabino ɗaya.” Sai na ce: “Ni ma zan taimaka masa da kwando ɗaya na dabino.” Sai ya ce: “Kin yi daidai kuma kin kyauta, ki tafi ki yi sadaka da shi a madadinsa, sannan ki yi wa ɗan baffanki wasiyya da alheri.” Sai ta ce: “Zan yi hakan.” [Ahmad #27319 da Abu Dawud #2214 da 2215, da Ibn Hibban #4279].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kiyayya ga Allah da Manzonsa (ﷺ) ita ce saɓa musu da bijire musu, musamman a kan manya-manyan al’amura, kamar waɗanda suka danganci kafirci da gaba da masoyansa.2. Duk waɗanda suka bijire wa Allah da Manzonsa (ﷺ) suka ƙi bin umarninsu ba su da wata hujja a wurin Allah ko wani hanzari, domin ya saukar musu da ayoyinsa bayyanannu masu sauƙin fahimta amma suka sa ƙafafunsu suka shure.3. Duk waɗanda suka shata wa kawunansu wasu iyakoki ba na Allah da Manzonsa ba, suka tsara wa kansu dokokin da suka ci karo da na Allah da Manzonsa (ﷺ), to waɗannan za su gamu da wulaƙanci da ƙasƙanci a duniya da lahira, kamar irin yadda ya faru ga kafirai na al’ummun da suka gabace su. Wannan albishir ne Allah yake yi wa muminai da cin nasara da samun ɗaukaka a kan maƙiyansu, matuƙar sun riƙe koyarwarsa da ta Manzonsa (ﷺ).4. Duk da cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗaukaka a saman dukkan halittunsa, ya daidaita a kan Al’arshinsa, to amma iliminsa yana ko’ina tare da kowa, ba abin da yake ɓuya a gare shi.

Suratul Mujadila (5-7)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحَآدُّونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ كُبِتُواْ كَمَا كُبِتَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ وَقَدۡ أَنزَلۡنَآ ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٖۚ وَلِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٞ مُّهِينٞ ۝٥ يَوۡمَ يَبۡعَثُهُمُ ٱللَّهُ جَمِيعٗا فَيُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُوٓاْۚ أَحۡصَىٰهُ ٱللَّهُ وَنَسُوهُۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ۝٦ أَلَمۡ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۖ مَا يَكُونُ مِن نَّجۡوَىٰ ثَلَٰثَةٍ إِلَّا هُوَ رَابِعُهُمۡ وَلَا خَمۡسَةٍ إِلَّا هُوَ سَادِسُهُمۡ وَلَآ أَدۡنَىٰ مِن ذَٰلِكَ وَلَآ أَكۡثَرَ إِلَّا هُوَ مَعَهُمۡ أَيۡنَ مَا كَانُواْۖ ثُمَّ يُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُواْ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٌ ۝٧

5. Lalle waɗanda suke saɓa wa Allah da Manzonsa an ƙaskantar da su kamar yadda aka ƙaskantar da waɗanda suke gabaninsu. Kuma haƙiƙa Mun saukar da ayoyi bayyanannu. Kafirai kuma suna da azaba mai wulaƙantarwa.

6. A ranar da Allah zai tashe su gaba ɗaya, sannan Ya ba su labarin abin da suka aikata. Allah Ya ƙididdige shi, su kuwa sun manta shi. Allah kuwa Mai ganin kowane abu ne.

7. Shin ba ka sani ba ne cewa Allah Ya san abin da yake cikin sammai da abi da yake cikin ƙasa? Babu wata ganawa tsakanin mutum uku da za ta faru sai Shi ne na huɗunsu, da kuma (tsakanin mutum) biyar sai Shi ne na shidansu, da kuma abin da ya kasa (haka) ko ya fi, sai Shi (Allah) Yana tare da su a duk inda suke; sannan Ya ba su labarin abin da suka aikata a ranar alƙiyama. Lalle Allah Masanin komai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan sakamakon waɗanda suke ƙin Allah da Manzonsa (ﷺ), da cewa an ƙaskantar da su kamar yadda aka ƙaskantar da al'ummun da suka gabata waɗanda suka nuna ƙiyayyarsu ga Allah da manzanninsa, tare da cewa ba su da wani uzuri na yin hakan. Domin ya saukar da ayoyi bayyanannu ga Manzonsa (ﷺ) amma duk da haka suka kafirce musu, to suna da azaba mai raɗaɗi a ranar alƙiyama, ranar da Allah zai tashe su gaba ɗaya, ba tare da ya bar ko ɗaya daga cikinsu ba, don yi musu sakayya game da ayyukansu, sai ya ba su labarin duk munanan ayyukansu a duniya, ya riga ya ƙididdige musu su, su kuwa sun manta, sai kwatsam su gan su a rubuce a cikin takardun ayyukansu waɗanda ba sa barin aiki ƙarami ko babba sai sun lissafa shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi haka ne domin shi masanin komai ne na ayyukansu, babu abin da zai ɓuya a gare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yalwar iliminsa wanda ya kewaye duk abubuwan da suke cikin sammai da ƙasa, na sarari da na ɓoye, inda ya ja hankalin Manzonsa (ﷺ) da cewa, bai lura da cewa shi Allah yana sane da duk abin da yake cikin sammai da wanda yake ƙasa babba da ƙarami ba, kuma babu mutum uku da za su keɓe suna ganawa face shi ne na huɗunsu da iliminsa; ko mutum biyar face shi ne na shidansu; ko adadinsu ya kasa haka ko ma ya fi haka, face yana tare da su da saninsa a duk inda suke, yana jin maganganunsu, sannan a ranar alƙiyama ya ba su labarin duk abin da suka aikata a duniya, domin shi masanin komai ne.

An karɓo daga Abu Musa Al'Ash'ari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Yayin da Manzon Allah (ﷺ) yake tafiya zuwa yaƙin Khaibara sai mutane suka tsinkayo wani kwazazzabo sai suka ɗaga muryoyinsu suna kabbara suna cewa: "*Allahu Akbar La'ilaha Illallahu.*" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce musu: "Ku sassauta wa kawunanku, domin ba kurma kuke kira ba ko wanda ba ya nan, domin kuna kiran mai ji ne, makusanci, yana nan tare da ku...." [Bukhari #4205 da 2704].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saboda kasancewar yawancin mutane sukan yi ganawarsu ne a kan saɓon Allah da shirya laifukan ta'addanci da keta dokar Allah, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da cewa su yi ganawarsu a kan ayyukan alheri da biyayya ga Allah da kiyaye haƙƙoƙin bayinsa da kauce wa saɓa masa, domin ana sa ran koyaushe a sami mumini mai bin dokar Allah da guje wa saɓonsa. Amma fajiri yakan yi wa dokokin Allah riƙon sakainar kashi, ba ya darajta shari'ar Allah ko ya kiyaye haƙƙin bayinsa.

2. Tsananin ƙiyayyar Yahudawa ga Manzon Allah (ﷺ) da muminai da shirye-shiryen makirci ga Musulmi a wuraren tarurrukansu da muhawarorinsu.

3. Haramcin ganawar Musulmi biyu ba tare da na ukunsu ba, domin yin hakan zai baƙanta masa rai.

4. Babbar manufar Shaiɗan a cikin muminai shi ne ya jefa su cikin abin da zai jawo musu ɓacin rai da damuwa.

5. Duk wani mai nufin cuta ba zai iya cutar da kowa ba sai da ƙaddarar Allah da yardarsa.

6. Wajibi ne ga mumini ya dogara ga Allah cikin dukkan al'amuransa, idan ya yi haka to Allah (ﷻ) ya ishe shi komai.

Suratul Mujadila (8-10)

أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ نُهُواْ عَنِ ٱلنَّجۡوَىٰ ثُمَّ يَعُودُونَ لِمَا نُهُواْ عَنۡهُ وَيَتَنَٰجَوۡنَ بِٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡعُدۡوَٰنِ وَمَعۡصِيَتِ ٱلرَّسُولِۖ وَإِذَا جَآءُوكَ حَيَّوۡكَ بِمَا لَمۡ يُحَيِّكَ بِهِ ٱللَّهُ وَيَقُولُونَ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ لَوۡلَا يُعَذِّبُنَا ٱللَّهُ بِمَا نَقُولُۚ حَسۡبُهُمۡ جَهَنَّمُ يَصۡلَوۡنَهَاۖ فَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ٨ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا تَنَٰجَيۡتُمۡ فَلَا تَتَنَٰجَوۡاْ بِٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡعُدۡوَٰنِ وَمَعۡصِيَتِ ٱلرَّسُولِ وَتَنَٰجَوۡاْ بِٱلۡبِرِّ وَٱلتَّقۡوَىٰۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِيٓ إِلَيۡهِ تُحۡشَرُونَ ٩ إِنَّمَا ٱلنَّجۡوَىٰ مِنَ ٱلشَّيۡطَٰنِ لِيَحۡزُنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَيۡسَ بِضَآرِّهِمۡ شَيۡـٔٗا إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١٠

8. Shin ba ka ga waɗanda aka hana su ganawa ba, sannan suke koma wa abin da aka hane su yinsa, suke kuma ganawa a kan saɓo da ta'addanci, da kuma saɓa wa Manzo? Idan kuma suka zo wurinka sai su gaishe ka da lafazin da Allah bai gaishe ka da shi ba, su riƙa cewa a ransu: "Me ya hana Allah Ya azabtar da mu saboda abin da muka faɗa?" Jahannama ta ishe su, za su shige ta; saboda haka makoma ta munana.

9. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan za ku gana to kada ku yi ganawar saɓo da ta'addanci da kuma saɓa wa Manzo. (A maimakon haka) ku gana a kan ayyukan alheri da taƙawa; kuma ku kiyaye dokokin Allah wanda zuwa gare Shi ne za a tattaro ku.

10. Ganawar (tasu) kawai daga Shaiɗan take, don ya baƙanta ran waɗanda suka yi imani, ba kuwa zai cuce su da komai ba sai da izinin Allah. Ga Allah ne kuma muminai za su dogara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin Manzonsa (ﷺ) game da mummunar ɗabi'ar Yahudawa ta ganawa da junansu, watau idan sun hango mumini sai su ƙeɓe wuri ɗaya su riƙa yin ƙus-ƙus a tsakaninsu don su jefa masa damuwa a ransa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana su aikata haka, amma kuma sai suka koma suka ci gaba da aikatawa, sukan kuma gana a tsakaninsu ne da maganganu da suke tattare da saɓon Allah, kamar giɓa, watau cin naman muminai, ko kuma shirya wani ta'addanci a kan muminai, ko saɓa wa Manzon Allah (ﷺ). Sannan kuma idan sun je wajen Manzon Allah (ﷺ) sai su riƙa gaishe shi da gaisuwar da Allah bai yi masa irinta ba, watau suna ce masa: "*Assamu Alaika"* ma'ana: 'Mutuwa ta tabbata a kanka', don su nuna cewa Annabi ba gaskiya yake faɗa ba da yake cewa shi Manzon Allah ne, har ma suna cika baki suna tutiya da cewa idan da gaske shi Annabi ne me ya hana Allah ya azabtar da su a kan maganar da suke faɗa masa? To tun da sun faɗa babu kuma abin da ya same su, wannan shi ya tabbatar musu cewa, shi ba Manzon Allah ne ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, ai talala ce yake yi musu ba ƙyale su ya yi ba, domin wutar Jahannama tana nan tana jiran su, kuma azabarta ta ishe su a kan mummunar kalmar da suke faɗa wa Manzonsa (ﷺ), za su ƙuna da zafinta, to tir da wannan makoma ta wutar Jahannama.

An karɓo daga A'isha, (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: "Wasu Yahudawa sun shigo wajen Annabi (ﷺ) sai suka ce masa: *"Assamu Alaika* ya baban Alƙasim!" Sai A'isha ta mayar musu da cewa: "*Wa Alaikumus Sam!*" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce mata: "Ya A'isha, Allah ba ya son alfasha da ƙaƙalo alfasha." Sai A'isha ta ce: "Ba ka ji su suna cewa: *'Assamu Alaika'* ba?"Sai ya ce: "Ni ba ki ji abin da nake faɗa ba: *'Wa Alaikum'*, watau

a kanku dai. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar." [Ibni Abi Hatim, dubi, Suyuɗi, *Ad-Durrul Mansur*, Juzu'i na 14, shafi na 319 da Bukhari #6024 da Muslim #2165].

An karƀo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Yahudawa suna ce wa Manzon Allah: *"Samun Alaika*" suna nufin zaginsa, sannan sai su riƙa faɗa a ransu cewa: "Me ya hana Allah ya yi mana azaba saboda abin da muke faɗa?" Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar." [Ahmad #6589 da 7061].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga muminai waɗanda suka yi imani da shi da kuma Manzonsa (ﷺ) tare da riƙe shari'arsa, ya hana su su kwaikwayi irin ɗabi'ar Yahudawa, watau kada su riƙa ganawa a tsakaninsu da abin da yake saƀon Allah ne ko shirin ta'addanci da saƀa wa Manzonsa (ﷺ); idan har za su yi wata ganawa a tsakaninsu, to su yi ta a kan aikin alheri da taƙawa, watau kiyaye dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne su bi umarninsa su kuma guji haninsa, domin sun san zuwa gare shi za a tattara su ranar alƙiyama, don ya yi musu hisabi da sakamako a kan ayyukansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wata ganawa wadda ta ƙunshi saƀon Allah da ta'addanci da saƀa wa Manzonsa (ﷺ) to wannan daga Shaiɗan ne, shi ne yake ƙawata wa masoyansa yana ingiza su da aikata hakan, ba don wani dalili ba sai kawai don ya shigar da baƙin ciki a zukatan muminai ya ƙuntata musu. To su sani cewa Shaiɗan duk makircinsa bai isa ya cutar da muminai da wani abu ba sai abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riga ya ƙaddara zai same su da izininsa, don haka sai muminai su dogara gare shi shi kaɗai a cikin dukkan al'amarinsu na addininsu da rayuwarsu.

An karƀo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan kun kasance ku uku, to kada biyu su shiga ganawa su bar ɗaya, domin yin haka zai baƙanta masa rai." [Bukhari #6290 da Muslim #2184].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin ladubban zama a majalisin ilimi a buɗa wa wanda ya zo daga baya don ya samu wurin zama ya amfana da ilimin.

2. Gwargwadon aikin mutum shi ne gwargwadon sakamakonsa, wannan yana daga cikar adalcin Ubangiji da ihsaninsa.

3. Falalar ilimi da masu ilimi, domin Allah yana ɗaukaka darajojinsu a dalilin imaninsu da iliminsu.

4. Idan majalisar ilimi ta cika sosai babu inda za a buɗa wa wasu su zauna, to ana iya tashin wasu don ɗaliban ilimi masu ɗaukar karatu su samu wuri kusa da malaminsu mai ba su karatu. Kuma yana daga cikin kyakkyawar tarbiya da ladabi idan aka nemi wani ya tashi don ba da wurin zamansa ga wani wanda zai amfana fiye da shi ta hanyar kusantar malamin, to ya yi haka ba tare da ya yi hushi ba, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗaga darajarsa a duniya da lahira. Amma idan ba haka ba, to ba ya halatta a tayar da wani daga mazauninsa don a zaunar da wani a wurin.

5. Ishara zuwa ga falalar sahabbai, domin sun kasance masu tsananin kwaɗayin zama kusa da Manzon Allah (ﷺ) domin sauraron hadisansa da samun falalar kusanci da shi.

6. Musulunci yana kwaɗaitar da 'ya'yansa a kan aikata duk wani abu da zai ƙara ƙaunar juna a tsakaninsu.

7. Duk wanda ya buɗa wa bayin Allah ƙofofin alheri shi ma Allah zai buɗa masa ƙofofin alheri duniya da lahira.

Suratul Mujadila (11)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا قِيلَ لَكُمۡ تَفَسَّحُواْ فِي ٱلۡمَجَٰلِسِ فَٱفۡسَحُواْ يَفۡسَحِ ٱللَّهُ لَكُمۡۖ وَإِذَا قِيلَ ٱنشُزُواْ فَٱنشُزُواْ يَرۡفَعِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡ وَٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ دَرَجَٰتٖۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ١١

11. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan aka ce da ku: “Ku yalwata a wuraren zama,” to sai ku yalwata, Allah zai yalwata muku; idan kuma aka ce: “Ku tashi (daga wurinku),” to sai ku tashi, Allah zai ɗaga darajojin waɗanda suka yi imani daga cikinku da waɗanda aka bai wa ilimi. Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya koyar da muminai ladabi na yadda za su kyautata wa junansu, musamman a majalisansu, inda ya kira su da siffarsu ta waɗanda suka yi imani da shi da kuma Manzonsa (ﷺ), ya umarce su da cewa, idan wasu da za su halarci majalisa daga baya, sai aka buƙaci a buɗa musu wuraren zama to su buɗa musu, su ma sai Allah ya buɗa musu a rayuwarsu ta duniya da ta lahira. Idan kuma an roƙe su da su tashi domin wani aiki na addini ko wata buƙata da ta taso, to su tashi ba tare da jin wata damuwa ko ƙorafi ba. Allah ya yi musu alkwarin cewa idan sun yi haka zai ɗaga darajojin waɗanda suka yi imani daga cikinsu da waɗanda aka ba su ilimi suka yi aiki da shi, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) masanin komai ne, zai kuma saka wa kowa gwargwadon aikinsa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya hana a tashi wani mutum daga mazauninsa sannan wani ya zauna a wurin, amma ku buɗa ku kuma yalwata. Ibn Umar ya kasance ba ya son wani ya tashi daga wurin zamansa don shi ya zauna a wurin. [Bukhari #6270 da Muslim #2177].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Kada mutum ya tashi wani daga wurin zamansa sannan shi ya zauna a wurin, sai dai su bubbuɗa su kuma yalwata.” [Bukhari #6269 da Muslim #2177].

Waɗannan hadisan suna nuna cewa idan mutum ya riga zama a wuri, to haƙƙinsa ne ya ci gaba da zama har sai ya ga dama ya tashi da kansa, kada a tilasta masa tashi don a zaunar da wani a wurin. Amma wannan ba ya hana idan an roke shi ya yi alfarma ya ba wa wani wurin zamansa ko ya buɗa masa don wata masalahar ya yi haka, domin yin haka shi ne kyautata ladabin zamantakewa da biyayya ga shugabanci wanda wannan ayar take jan hankali a kansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An sa wa Musulmi tsananin son yawan ganawa da Manzon Allah (ﷺ) don samun kusanci da shi da yi masa tambayoyi a kan sha’anin addininsu da rayuwarsu; wannan yakan shagaltar da shi a yawancin lokutansa (ﷺ). Shi kuma yana da muhimman abubuwa a gabansa; yana buƙatar lokacin isar da saƙo da lokutan ibada da na wasu al’amuran da suka shafe shi da na iyalinsa da na hutu da kaɗaita da Ubangijinsa. Don haka waɗannan ayoyi suka sauka suna umarni da a gabatar da sadaka kafin ganawa da Manzon Allah (ﷺ) domin amfanin da ke cikin yin haka, kuma a rage yawan wannan ganawar, musamman da yake ƙalilan ne suke da halin ba da sadakar.

2. Tun farko Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta bayar da sadakar ne a kan wanda yake da abin bayarwa kafin ya ɗauke wa waɗanda ba su da abin yin sadaka.

3. Daga cikin amfanin wannan sadakar akwai taimaka wa mabuƙata da abin da za su ci su toshe buƙatarsu ta lalura, musamman a lokacin faƙirai suna da yawa a Madina, kamar mutanen Suffa da waɗanda suka yiwo hijira daga Makka da sauran garuruwa suka baro dukiyoyinsu da gidajensu.

4. Daga cikin hikimar wannan sadakar akwai bambance tsakanin muminai na gaskiya masu son Allah da Manzonsa da kwaɗayin ilimi da alheri da kuma waɗanda son dukiyoyinsu ya mamaye musu zukata, waɗanda ba za su yarda su ba da dukiyoyinsu don su gana da Manzon Allah (ﷺ) ba.

5. Kara fahimtar girman Manzon Allah da martabarsa, domin duk abin da aka samu bayan an sha wuya ba daidai yake da wanda aka samu a ɓagwas ba.

6. Nuna yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake tausaya wa Manzonsa (ﷺ).

Suratul Mujadila (12-13)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا نَٰجَيۡتُمُ ٱلرَّسُولَ فَقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيۡ نَجۡوَىٰكُمۡ صَدَقَةٗۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ لَّكُمۡ وَأَطۡهَرُۚ فَإِن لَّمۡ تَجِدُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ١٢ ءَأَشۡفَقۡتُمۡ أَن تُقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيۡ نَجۡوَىٰكُمۡ صَدَقَٰتٖۚ فَإِذۡ لَمۡ تَفۡعَلُواْ وَتَابَ ٱللَّهُ عَلَيۡكُمۡ فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥۚ وَٱللَّهُ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٣

12. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan za ku gana da Manzo, to sai ku gabatar da wata sadaka kafin ganawar taku. Wannan shi ya fi muku alheri da tsarkaka. Sannan idan ba ku samu ba, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai rahama.

13. Yanzu kun samu damuwa ne ta gabatar da sadaka kafin ganawarku? To idan ba ku aikata haka ba Allah kuma ya karɓi tubarku, to sai ku tsayar da salla, ku ba da zakka, ku kuma bi Allah da Manzonsa. Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne.

Sahabban Manzon Allah (ﷺ) koyaushe suna matuƙar ƙaunar ganawa da shi, domin suna son jin maganarsa da kuma samun albarkar kusantarsa. Wannan kuwa ya zamanto yana wahalar da Manzon Allah (ﷺ) yana kuma ɗaukar masa lokacinsa da yawa. To shi ne a waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai masu son ganawa da Manzonsa (ﷺ) da su fara gabatar da sadaka ga miskinai kafin ganawar, domin ta haka ne za su sami alheri mai yawa da tsarkaka daga zunubansu da kurakuransu, kuma zukatansu su tsarkaka da ɗa'ar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). To kuma wannan sadakar ba dole ce a kan kowa ba, ta taƙaita ne a kan masu hali, amma miskinai da suke son ganawa da Manzon Allah (ﷺ) kuma ba su sami abin da za su gabatar na sadaka ba, to Allah bai ƙuntata musu ba, ya yafe musu bayar da wannan sadakar; suna iya ganawa da Manzo (ﷺ) ba tare da sun bayar da komai ba, domin shi mai rahama ne ga bayinsa ba ya ɗora musu abin da ya fi ƙarfinsu.
To yayin da gabatar da sadaka gabanin ganawa da Manzon Allah (ﷺ) ta yi wa muminai wahala sosai, har sun fara tsoron talauci, saboda yawan sadakar da za su riƙa bayarwa ga msikinai duk sanda suka tashi ganawa da Manzon Allah (ﷺ), sai Allah ya sassauta musu wannan hukuncin, ya ɗauke musu bayar da wannan sadakar ya karɓi tubansu, don haka sai ya umarce su da su tsayar da salla yadda ya dace, su fitar da zakkar dukiyoyinsu, su bi Allah su bi Manzonsa (ﷺ), kuma su tuna cewa Allah masanin duk abubuwan da suke aikatawa ne, zai kuma yi musu sakamako a kansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yahudawa mutane ne da Allah ya yi hushi da su, don haka duk wanda ya yi ƙawance da su to ya jefa kansa a cikin hushin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Tabbatar da samuwar ƙawance da haɗin kai tsakanin Yahudawa da munafukan cikin wannan al'umma.

3. Munafukai ko da sun yi rayuwa tare da Manzon Allah (ﷺ) sun kuma bayyana Musulunci a sarari, to amma ba sa cikin sahabbansa, don haka lissafa su a cikin sahabbai ƙaryata ayar Allah ne.

4. Rantsuwa a kan ƙarya da gangan siffa ce ta munafukai.

5. Tsananin azabar munafukai a ranar alƙiyama.

6. Daga cikin miyagun ayyukan munafukai akwai hana mutane karɓar gaskiya da daƙile duk wani mai nufin aikata alheri da sage masa gwiwa. A duk lokacin da suka ga wani yana shirin karɓar Musulunci sai su shiga kushe addinin, suna ɓata shi a wurinsa. Wanda kuma ya kula da yadda suke yin rantse-rantse na ƙarya kuma buƙatarsu tana biya, kamar samun wata ɗaukaka a wajen mutane, to sai ka ga ya fara kwaikwayon ɗabi'arsu, ya rungumi salon rayuwa irin tasu.

7. Duk abin da mutum ya rayu a kansa, to a kansa ne za a tashe shi ranar alƙiyama.

8. Kada munafukai su yi tsammani cewa kamar yadda a nan duniya suka riƙa amfani da rantsuwa suna kuɓuta daga horo, hakanan ma a lahira idan sun rantse wa Allah a kan ƙarya za a ƙyale su su tafiyarsu abinsu ruwa ta sha; ko kusa ba haka ne ba. Rantsuwarsu a lahira ba za ta tsinana musu komai ba sai ƙarin azabar Allah a gare su.

9. Rashin tunawa da Allah da rashin ambatonsa sakamako ne na galabar Shaiɗan a kan bawa.

Suratul Mujadila (14-19)

۞أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ تَوَلَّوۡاْ قَوۡمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مَّا هُم مِّنكُمۡ وَلَا مِنۡهُمۡ وَيَحۡلِفُونَ عَلَى ٱلۡكَذِبِ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٤ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُمۡ عَذَابٗا شَدِيدًاۖ إِنَّهُمۡ سَآءَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٥ ٱتَّخَذُوٓاْ أَيۡمَٰنَهُمۡ جُنَّةٗ فَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ فَلَهُمۡ عَذَابٞ مُّهِينٞ ١٦ لَّن تُغۡنِيَ عَنۡهُمۡ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗاۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١٧ يَوۡمَ يَبۡعَثُهُمُ ٱللَّهُ جَمِيعٗا فَيَحۡلِفُونَ لَهُۥ كَمَا يَحۡلِفُونَ لَكُمۡ وَيَحۡسَبُونَ أَنَّهُمۡ عَلَىٰ شَيۡءٍۚ أَلَآ إِنَّهُمۡ هُمُ ٱلۡكَٰذِبُونَ ١٨ ٱسۡتَحۡوَذَ عَلَيۡهِمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ فَأَنسَىٰهُمۡ ذِكۡرَ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ حِزۡبُ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ أَلَآ إِنَّ حِزۡبَ ٱلشَّيۡطَٰنِ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ١٩

14. Shin ba ka ga waɗanda suka yi abota da wasu mutane da Allah Ya yi fushi da su ba, su ba cikinku suke ba, ba kuma cikinsu suke ba; su kuma riƙa rantsuwa a kan ƙarya, alhali kuwa su suna sane (da yin ta)?

15. Allah Ya tanadar musu azaba mai tsanani, lalle su abin da suke aikatawa ya munana.

16. Sun ɗauki rantse-rantsensu su zama garkuwa, sai suka kange hanyar Allah, saboda haka suna da (sakamakon) azaba mai wulaƙantarwa.

17. Dukiyoyinsu da ‘ya’yansu ba za su amfanar musu komai ba a wurin Allah. Waɗannan su ne ‘yan wuta; su madawwama ne a cikinta.

18. A ranar da Allah zai tashe su baki ɗaya sai su rantse Masa kamar yadda suke rantse muku, su kuma riƙa tsammanin su sun yi wani abu (mai amfani). Ku saurara, lalle kam su ne maƙaryata.

19. Shaiɗan ya ci ƙarfinsu, sai ya mantar da su ambaton Allah. Waɗannan su ne ƙungiyar Shaiɗan. Ku saurara, lalle ƙungiyar Shaiɗan su ne taɓaɓɓu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani mummunan hali na munafukai waɗanda suke abota da Yahudawa waɗanda Allah ya yi fushi da su saboda kafircinsu da laifuffukansu, ga shi kuma su ba daga cikin muminai suke ba, domin addini ya raba su, kuma ba daga cikin Yahudawan suke ba, domin su ma addini ya raba tsakaninsu sannan jinsinsu ba ɗaya ne ba, domin su munafukai Larabawa ne mutanen Madina, su kuma Yahudawa Isra’ilawa ne baƙi a Madina. Kuma duk da wannan zagon ƙasa da suke yi wa Musulunci, suna yi wa Musulmi rantsuwa da cewa su ma lalle Musulmi ne, wai kuma ba sa kai wa Yahudawa labarin Musulmi, alhalin ƙarya suke yi, kuma su ba muminai ne ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu tanadin azaba mai tsanani a lahira lokacin da zai jefa su can ƙarƙashin wutar Jahannama, domin mummunan aikin da suka yi a duniya na kafirci da munafurci da yi wa Musulmi zagon ƙasa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, munafukai sun mayar da rantse-rantsensu da suke yi a gaban Musulmi wata garkuwa ce da suke fakewa da ita, don gudun kada a kashe su idan yaƙi ya ɓarke tsakanin Musulmi da kafirai, don haka sai suke bayyana Musuluncinsu a fili suke ɓoye kafircinsu a zuciya, saboda haka ba za a taɓa su ba, ba kuma za a taɓa dukiyoyinsu ba, sai su tsira da rayuwarsu da dukiyoyinsu. Wannan ya ba su damar ci gaba da zama a tsakiyar muminai sai suka ci gaba da kange mutane daga hanyar Allah, don haka suna da azaba mai wulaƙantarwa, sakamakon rashin imaninsu da Allah da rashin miƙa wuya ga umarninsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, tarin dukiya da yawan ‘ya’ya da suke tinƙaho da shi a duniya ba zai amfana musu komai ba a lahira yayin da za su ga azabar Allah. Waɗannan su ne ‘yan wuta waɗanda za su dawwama a cikinta har abada babu ranar fita, kuma azaba ba za ta taɓa yanke musu ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan mummunan hali da munafukai suka rayu a kansa a nan duniya, da shi za su tashi a ranar alƙiyama, ranar da Allah zai tashi kowa a cikinta domin yi masa sakamako; to a ranar ne za su dinga yi wa Allah rantsuwa cewa su ba su taɓa aikata kafirci ko munafurci ba, wai su muminai ne masu aiki da abin da Allah ya umarce su da shi. Za su yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) rantsuwa a lahira kamar yadda suke yi wa muminai rantsuwa a duniya, su tabbatar musu cewa, su fa Musulmi ne, tsammaninsu wannan rantsuwar za ta yi musu wani amfani ko ta kare musu wata azaba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, lalle su maƙaryata ne a duniya da lahira, sun riga sun sayi ɓata da shiriyar da Allah ya nuna musu, sun zaɓi shiga wuta a kan shiga Aljanna, domin Shaiɗan ya riga ya yi galaba a kansu ya cika musu zukatansu da waswasi har ya mantar da su tunawa da Allah da ambatonsa, don haka sun ƙi aikata abin da zai yarda da su, sun rungumi ayyukan da suke fusatar da shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lalle masu waɗannan siffofi su ne ƙungiyar Shaiɗan kuma mabiyansa sau da ƙafa, kuma tabbas ƙungiyar Shaiɗan su ne asararru duniya da lahira.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sunnar Allah ce da ya riga ya zartar cewa kafirai ba za su taɓa yin galaba ba a kan muminai, ko da sun fi ƙarfinsu a wani lokaci, to ɗan lokaci ne ƙanƙani, nasarar Allah tana tafe.

2. Duk wani mai imani na gaskiya ba zai taɓa nuna ƙaunarsa da jiɓintarsa ga waɗanda suke gaba da Allah da Manzonsa ba komai kusancinsa da su, domin ƙaunar Allah da Manzonsa tana gaba da komai.

3. Duk wata soyayya da za ta sa Musulmi ya ƙaunaci addinin kafiri, to wannan soyayyar haramun ce. Amma soyayya ta ɗabi'a, kamar ta tsakanin ɗa da iyayensa ko makusantansa, wannan ba haramun ce ba.

Suratul Mujadila (20-22)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحَآدُّونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ أُوْلَٰٓئِكَ فِى ٱلْأَذَلِّينَ ﴿٢٠﴾ كَتَبَ ٱللَّهُ لَأَغْلِبَنَّ أَنَا۠ وَرُسُلِىٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِىٌّ عَزِيزٌ ﴿٢١﴾ لَّا تَجِدُ قَوْمًا يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ يُوَآدُّونَ مَنْ حَآدَّ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَوْ كَانُوٓا۟ ءَابَآءَهُمْ أَوْ أَبْنَآءَهُمْ أَوْ إِخْوَٰنَهُمْ أَوْ عَشِيرَتَهُمْ ۚ أُوْلَٰٓئِكَ كَتَبَ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلْإِيمَٰنَ وَأَيَّدَهُم بِرُوحٍ مِّنْهُ ۖ وَيُدْخِلُهُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۚ رَضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ ۚ أُوْلَٰٓئِكَ حِزْبُ ٱللَّهِ ۚ أَلَآ إِنَّ حِزْبَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿٢٢﴾

20. Lalle waɗanda suke saba wa Allah da Manzonsa waɗannan suna cikin mafiya ƙasƙanci.

21. Allah Ya rubuta cewa: Lalle Ni da manzannina ne za mu yi galaba. Lalle Allah Mai ƙarfi ne, Mabuwayi.

22. Ba za ka taba samun wasu mutane da suke yin imani da Allah da ranar lahira ba, su riƙa ƙaunar waɗanda suke gaba da Allah da Manzonsa, ko da kuwa sun kasance iyayensu ne ko 'ya'yansu ko 'yan'uwansu ko kuma danginsu. Waɗannan Allah Ya rubuta imani a cikin zukatansu, Ya kuma ƙarfafe su da wani ruhi daga wurinsa; zai kuma shigar da su gidajen Aljanna (waɗanda) ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, madawwama a cikinsu. Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi. Waɗannan ne ƙungiyar Allah. Ku saurara, lalle ƙungiyar Allah su ne masu samun babban rabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana narkonsa da mummunan sakamako ga waɗanda suke gaba da Allah da Manzonsa suke saba wa umarninsu ta hanyar aikata kafirci da munafurci, ya tabbatar musu cewa, suna cikin waɗanda ya ƙasƙantar da su duniya da lahira zai kuma wulaƙanta su kamar yadda ya wulaƙanta kafiran da suka gabace su.Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi rantsuwa cewa tabbas shi da manzanninsa su ne za su yi nasara da ƙarfin hujja da kuma a fagen daga, domin Allah mai ƙarfi ne zai iya taimakon manzanninsa da ƙarfinsa, kuma mabuwayi ne, babu wanda zai ja da shi ya kai labari.

A ayar ƙarshe ta wannan Surar kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, ba zai taba samun wasu mutane da suka yi imani da Allah da ranar lahira ba, a same su suna son wanda yake gaba da Allah da Manzonsa suna jiɓintar al'amarinsa, ko da kuwa su maƙiyan na Allah da Manzonsa iyayensu ne ko 'ya'yansu ko 'yan'uwansu ko danginsu, domin imaninsu ba zai bar su su so maƙiyan Allah da Manzonsa (ﷺ) ba har su riƙa jiɓintar al'amuransu, kuma sun san cewa dangantakar imani sama take da duk wata dangantaka. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mutane masu irin wannan siffar su ne waɗanda ya tabbatar da imani wanda ba zai girgiza ba a cikin zukatansu, ya kuma ƙarfafe su da wata hujja daga wajensa da haske. A ranar alƙiyama kuma zai shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudu ta ƙarƙashinsu, za su kuma dawwama a cikinsu har abada, suna cikin ni'imomin da ba za su yanke ba. Kuma Allah ya yarda da su, ba zai yi fushi da su ba har abada, su ma sun yarda da shi sun gamsu da sakamakon da ya yi musu da ni'imomin da ya tanadar musu a ciki, mafi girman ni'imominsa gare su kuwa shi ne ganin Zatinsa (Mai tsarki da ɗaukaka). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan su ne ƙungiyar Allah, su ne kuma masu samun babban rabo a duniya da lahira, domin Allah zai tserar da su daga duk abin da suke ƙi, zai kuma haɗa su da duk abin da suke so.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wani da Allah ya halitta a ƙasa da sama suna yi masa tasbihi ne tare da tsarkake shi.

2. Maɓarnata sukan yi ƙarfin da har za a riƙa zaton cewa ba za a iya samun galaba a kansu ba, sai kuma ka ga Allah ya kawo abin da zai karya su ta inda ba sa zato.

3. Duk wanda ya dogara da wani abu ba Allah ba, to ya yi saki reshe kama ganye.

4. Yana daga cikin ƙaddarar Allah ga mutane ya ture musu manyan musibu ya saukar musu waɗanda ba su kai su tsanani ba.

5. Natsuwar zukata da ƙarfinsu wata alama ce ta samun nasara a kan abokan gaba. Yayin kuma da tsoro ya mamaye zukata, to shi ma alama ce da take nuna lalle karaya ta zo.

6. Yin umarni da aiki da lura da ƙiyasin abu da wani abu mai kama da shi da nazari a kan hikimomin da ke ƙunshe a cikin hukunce-hukuncen shari’a, waɗanda hankali zai iya riskar su, abu ne da shari'a ta tabbatar da shi.

7. Haɗarin da yake cikin saɓa wa Allah da Manzonsa (ﷺ) da tsananin uƙubar Allah ga wanda ya aikata haka.



59-Suratul Hashr

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan da ta shahara da shi shi ne '*Suratul Hashri*'. Amma Abdullahi ɗan Abbas ya kira ta da '*Suratu Banin Nadhir*'. An kira ta da '*Suratul Hashri'* ne kuma saboda lafazin *'Al-Hashr'* da ya zo a cikinta a aya ta 2, wanda yake nufin fitar da Yahudawan Banin Nadhir daga Madina. Ibn Abbas kuma ya ambace ta da sunan *'Suratu Banin Nadhir'* ne saboda a cikinta Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarinsu.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Babu wani saɓani a tsakanin malamai game da cewa Sura ce *Madaniyya*.

3. Jerin Saukarta
Ita ce Sura ta tasa'in da takwas (98) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Bayyina*' kafin '*Suratun Nasar*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta ashirin da huɗu ne (24) ba tare da wani saɓani ba.

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin ƙarfin Allah da buwayarsa wajen dankwafar da Yahudawa da abokansu munafukai da bayanin rarrabuwar kansu da haɗin kan muminai.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Gamewar mulkin Allah ga dukkan abin da yake sama da wanda yake ƙasa.
• Ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Musulmi ta fitar musu da Yahudawa daga garin Madina duk da irin ƙarfinsu da tsaro da suke tinƙaho da shi.
• Bayanin hukunce-hukuncen dukiyoyin Yahudawa da suka bari da waɗanda suka lalata da taimakon Musulmi.
• Falalar sahabbai masu hijira (*Al-Muhajirun*) da mutanen Madina (*Al-Ansar*) da wajabcin nuna musu ƙauna da girmamawa.
• Tona asirin munafukai bayan sun yi wa Yahudawa alƙawarin ƙarya na za su taimake su wajen yaƙar Musulmi.
• Tsananin tsoron Yahudawa da munafukai da rashin haɗin kai a tsakaninsu.
• Umartar muminai da su zama masu taƙawa masu kyakkyawan tanadi don gobe alƙiyama.
• Bayanin girman Alƙur'ani da irin yadda yake kimsa tsoron Allah da ƙaskantar da kai gare shi, ba ga mutane kaɗai ba har ma da duwatsu.
• Bayanin wasu siffofin Allah masu girma da tsarkakewar sammai da ƙasa a gare shi.

Suratul Hashr (1-4)

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ۝١ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَخۡرَجَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ مِن دِيَٰرِهِمۡ لِأَوَّلِ ٱلۡحَشۡرِۚ مَا ظَنَنتُمۡ أَن يَخۡرُجُواْۖ وَظَنُّوٓاْ أَنَّهُم مَّانِعَتُهُمۡ حُصُونُهُم مِّنَ ٱللَّهِ فَأَتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِنۡ حَيۡثُ لَمۡ يَحۡتَسِبُواْۖ وَقَذَفَ فِي قُلُوبِهِمُ ٱلرُّعۡبَ يُخۡرِبُونَ بُيُوتَهُم بِأَيۡدِيهِمۡ وَأَيۡدِي ٱلۡمُؤۡمِنِينَ فَٱعۡتَبِرُواْ يَٰٓأُوْلِي ٱلۡأَبۡصَٰرِ ۝٢ وَلَوۡلَآ أَن كَتَبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمُ ٱلۡجَلَآءَ لَعَذَّبَهُمۡ فِي ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ عَذَابُ ٱلنَّارِ ۝٣ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ شَآقُّواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥۖ وَمَن يُشَآقِّ ٱللَّهَ فَإِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ۝٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa ya tsarkake Allah; Shi ne kuwa Mabuwayi, Mai hikima.

2. Shi ne wanda Ya fitar da waɗanda suka kafirce daga ma'abota littafi daga gidajensu a fitarwa ta farko. Ba ku yi tsammanin cewa za su fita ba, su kuma sun zaci ganuwoyinsu za su kare su daga Allah, sai Allah Ya zo musu ta inda ba su yi tsammani ba; Ya kuma jefa tsoro a cikin zukatansu. Suka riƙa rushe gidajensu da hannayensu da kuma hannayen muminai, to sai ku luru da kyau ya ku ma'abota basira.

3. Ba don Allah Ya ƙaddara musu ficewa ba, lalle da Ya azabtar da su a duniya, a lahira kuma suna da azabar wuta.

4. Wannan kuwa saboda cewa sun saɓa wa Allah da Manzonsa ne, duk kuwa wanda ya saɓa wa Allah da Manzonsa, to lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da bayyana cewa, duk abin da yake cikin sammai da wanda yake ƙasa sun tsarkake Allah daga duk wani abu da bai dace da shi ba, domin shi Mabuwayi ne da babu mai iya tunkarar sa, mai hikima ne a cikin halittarsa da Kaddararsa da shari'arsa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin Yahudawan Banun Nadhir waɗanda suka kafirce masa da Manzonsa (ﷺ), har ma suka shirya makircin hallaka Manzo (ﷺ).
Yahudawa waɗanda suke tare da Annabi (ﷺ) a Madina sun ƙulla yarjejeniya da shi tun isowarsa Madina a kan abubuwa da dama da suka danganci zamantakewa tare. Daga cikin abubuwan da suka ƙulla alƙawari a kai, akwai cewa idan wata fitina za ta tunkaro su daga waje to za su haɗa kai gaba ɗaya su tunkare ta. Akwai wani sahabin Annabi (ﷺ) mai suna Amru ɗan Umayya Al-Dhamri ya kashe wasu mutanen Makka su biyu bisa kuskure, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ɗauki alƙawarin biyan diyyoyinsu, sai ya tafi shi da wasu sahabbansa zuwa Yahudawan Banun Nadhir don ya karɓo abin da za su taimaka da shi na dukiyar diyyar. Suka yi masa alƙawarin za su tattaro masa, suka neme shi da ya samu wuri ya zauna har su kammala tattara masa dukiyar. Daga nan sai wasu daga cikinsu suka keɓe suka tattauna a kan irin makircin da za su ƙulla wa Manzon Allah (ﷺ), Shaiɗan kuma ya raɗa musu cewa kawai su yi amfani da wannan damar su kashe shi su huta. Suka tambayi junansu cewa, wane ne a cikinsu zai iya ɗaukar dutsen niƙa ya hau kan bishiyar da Manzon Allah yake zaune a ƙarƙashinta ya jefo masa shi don ya hallaka shi? Sai wani shaƙiyyi daga cikinsu ya ce shi zai iya, amma sai aka samu wani mai ɗan hankali daga cikinsu ya yi musu kashedin cewa, kada su kuskura su ce za su yi wannan ɗanyen aiki, domin idan sun yi haka, to sun warware alƙawarin da suka ƙulla da Manzon Allah (ﷺ). Amma suka nuna masa ba za su fasa abin da suka yi niyya ba.
A nan ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko wa Manzonsa (ﷺ) wahayi na irin abin da Yahudawan Banun Nadhir suke shirin yi masa, sai nan take ya tashi da gaggawa ya nufi cikin garin Madina, sahabbansa kuma suka bi shi daga baya, ya ba su labarin aika-aikar da Yahudawa suka shirya yi.

Sai Manzon Allah (ﷺ) ya aika musu cewa, lalle su tattara ya nasu-ya nasu su fita daga garin Madina, ba zai bar su su ci gaba da zama a cikinta ba har abada. Har sun yarda sun fara shirye-shiryen ficewa daga Madina sai shugaban munafukai Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salulu ya aika musu da cewa, su yi zamansu kada su fita, kuma shi da jama'arsa lalle suna tare da su suna goyon bayansu, kuma a shirye suke su taimaka musu idan yaƙi ya ɓarke tsakaninsu da Musulmi. Daga nan sai suka fasa fita suka nuna taurin kansu.
Sai Annabi (ﷺ) ya yi umarni da a kewaye gidajensu, aka yi musu ƙofar raggo, ya kuma yaƙe su ya sassare itatuwan dabinonsu ya ƙona su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya jefa tsoro a zukatansu bayan munafukai sun ƙi cika musu alƙawarin da suka yi musu na taimako. Daga ƙarshe suka aika wa Manzon Allah (ﷺ) cewa sun amince da hukuncinsa, sun yarda za su fice daga Madina. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya amince su fice su da iyalansu da kayayyakin da raƙumansu za su iya ɗauka in ban da makamai. Suka fita suka nufi ƙasar Sham.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, shi ne wanda ya fitar da Yahudawan Banun Nadhir daga gidajensu a Madina a rukunin fitarwa ta farko zuwa Sham bayan sun warware alƙawarinsu da Manzon Allah (ﷺ) da haɗa kansu da mushirikai don yaƙar Musulmi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, muminai ba su taɓa zaton cewa waɗannan Yahudawa za su bar gidajensu ba, saboda ƙarfin tsaro da isasshen tanadin kariya da suke da shi. Su ma kansu Yahudawan, sun yi zaton cewa manya-manyan ganuwoyi masu ƙarfi da suka gina za su kare su daga uƙubar Allah idan ta zo musu, to sai ga shi azabar Allah ta zo musu ta inda ba su yi tsammanin zuwanta ba, yayin da Manzon Allah (ﷺ) ya ba da umarnin a yaƙe su, a fitar da su daga garin Madina. Allah kuma ya shigar da matsanancin tsoro a zukatansu, suka riƙa rushe gidajensu ta ciki da hannayensu, domin kada Musulmi su amfana da su, ta waje kuma Musulmi ne suka yi ta rushe su. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga masu hankali da basira da su ɗauki izina daga wannan azaba da ta auka wa waɗannan Yahudawa saboda kafircinsu da mugun nufinsu, don haka kada wasu su kuskura su kwatanta irin aikinsu, sai su ma su haɗu da azabar Allah irin wannan.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya ma yi rangwame ne ga waɗannan kafiran, ba don ya riga ya rubuta musu fitarwa daga gidajensu ba, to da lalle ya azabtar da su a duniya ta hanyar kisa da bauta, watau kamar yadda ya yi wa 'yan'uwansu Banu Kuraiza. A lahira kuwa akwai azabar wuta tana nan tana jiran su, za su shige ta su dawwama a cikinta har abada.Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan sakamakon azabtarwa ya same su ne saboda sun saɓa wa Allah da Manzonsa (ﷺ), sun nuna musu ƙiyayya a sarari ta hanyar kafirci da warware alƙawari; duk wanda kuwa ya nuna ƙiyayyarsa ga Allah, to ya sani lalle Allah mai tsananin uƙuba ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Musulmi izini su sassare itatuwan dabinai na Yahudawan Banun Nadhir, domin ƙarin wulaƙanci da ƙasƙanci a gare su da nuna musu kasawarsu da raggwancinsu wajen gaza kare dukiyoyinsu; suna gani ana lalata su babu yadda suka iya.

2. Asali ba a yarda a lalata dukiyar abokin gaba ba, to amma wani lokaci akan iya yin haka saboda wata maslaha babba, kamar samar wa da mayaƙa sansani, ko jefa tsoro da firgici a zukatan abokan gaba, ko wani abu da maslahar yaƙi takan iya hukuntawa.

3. Bayanin kason dukiyar '*fai'u*', watau dukiyar da Musulmi suka samu daga kafirai ba tare da an gwabza yaƙi ba.

4. Wajabcin karɓar duk abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi wanda ya shafi shikashikan addini da hukunce-hukuncensa na sarari da na ɓoye. Riƙo da Sunnar Manzon Allah (ﷺ) riƙo ne da Alƙur'ani mai girma, saɓa mata ma saɓa wa Alƙur'ani ne.

Suratul Hashr (5-7)

مَا قَطَعْتُم مِّن لِّينَةٍ أَوْ تَرَكْتُمُوهَا قَآئِمَةً عَلَىٰٓ أُصُولِهَا فَبِإِذْنِ ٱللَّهِ وَلِيُخْزِىَ ٱلْفَـٰسِقِينَ ۝٥ وَمَآ أَفَآءَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ مِنْهُمْ فَمَآ أَوْجَفْتُمْ عَلَيْهِ
مِنْ خَيْلٍ وَلَا رِكَابٍ وَلَـٰكِنَّ ٱللَّهَ يُسَلِّطُ رُسُلَهُۥ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ ۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ۝٦ مَّآ أَفَآءَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ مِنْ أَهْلِ ٱلْقُرَىٰ فَلِلَّهِ
وَلِلرَّسُولِ وَلِذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَـٰمَىٰ وَٱلْمَسَـٰكِينِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِ كَىْ لَا يَكُونَ دُولَةًۢ بَيْنَ ٱلْأَغْنِيَآءِ مِنكُمْ ۚ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا
نَهَىٰكُمْ عَنْهُ فَٱنتَهُوا۟ ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ۝٧

5. Duk abin da kuka sare na wata bishiyar dabino ko kuka bar ta a tsaye a kan tushiyoyinta, to da izinin Allah ne, don kuma Ya kunyata fasiƙai.

6. Kuma duk abin da Allah Ya bai wa Manzonsa na wata dukiya tasu (don falalarsa), to ba wani hari kuka kai na dawaki ko raƙuma ba saboda shi, sai dai kuma Allah Shi ne Yake ɗora manzanninsa a kan wanda Ya ga dama. Allah kuwa Mai iko ne a kan komai.

7. Abin da Allah ya bai wa Manzonsa na wata dukiya daga mutanen alƙaryu, to na Allah ne da Manzonsa da kuma danginsa na kusa da marayu da miskinai da matafiyin (da guzuri ya yanke wa), don kada ya zama mai juyawa tsakanin mawadata daga cikinku. Kuma abin da Manzo ya ba ku sai ku karɓe shi, abin kuma da ya hana ku sai ku hanu. Ku kuma kiyaye dokokin Allah; lalle Allah Mai tsananin uƙuba ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Musulmi cewa dabinan da suka sassare a lokacin yaƙi da Yahudawan Banun Nadhir don su ƙara cusa musu baƙin ciki, ko waɗanda suka bar su a tsaye a kan tushiyoyinsu domin su amfana da su, to sun yi wannan ne duka da izinin Allah da umarninsa, ba su yi gaban kansu ba, ba kuma sun yi haka ne don ɓarnata dukiya ba, kamar yadda Yahudawan suka riƙa yayatawa don su soki Musulmi da shi, ba su kuma san cewa Allah ne ya yi musu umarni da haka ba, Allah kuma ya yi haka ne domin ya wulaƙanta fasiƙai, watau Yahudawa masu bijire wa dokokinsa da shirya makirce-makirce don cutar da Manzonsa da karya alƙawarin zamantakewa da suka ɗauka.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Musulmi cewa, dukiyar Yahudawan Banun Nadhir da ya dawo wa Manzonsa ita su Musulmi suna sane da cewa ba su kai wani hari da dawakansu ko raƙumansu ba, ba su kuma sha wata wahala wajan samun ta ba, Allah ne kawai yake ɗora manzanninsa a kan wanda ya ga dama, don babu abin da ya fi ƙarfinsa, saboda haka ya ɗora Manzonsa (ﷺ) a kan Yahudawan Banun Nadhir ya kuma ci nasara a kansu ba tare da wani yaƙi na a zo a gani ya auku ba, domin shi Allah mai iko ne a kan komai, babu abin da zai gagare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kasafin dukiyar ganimar da ya ba wa Manzonsa a wannan yaƙi, inda ya bayyana cewa, dukiyar gaba ɗayanta ta Allah ce, yana bayar da ita ga wanda ya so, don haka ya mallaka ta ga Manzonsa (ﷺ) da danginsa na kusa, watau Banu Hashim da Banul Muɗɗalib waɗanda aka haramta wa cin dukiyar sadaka, da kuma marayu da miskinai da matafiyan da guzurinsu ya yanke. Allah kuma ya yi wannan kasafin ne don kada dukiyoyi su yi ta jujjuyawa tsakanin mawadata kaɗai ba sa kaiwa ga talaka marar ƙarfi. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Musulmi cewa su karɓi abin da Annabi (ﷺ) ya ba su daga cikin dukiyar ganima da aka samu ba tare da yaƙi ba (watau *fai'u*), abin da kuma ya hana su sai su hanu, watau su nisance shi, kuma su kiyaye dokokinsa, ta hanyar aikata abin da ya umarce su da barin abin da ya hana su; su kuma guji abin da zai jawo musu uƙubar Allah, domin Allah mai tsananin uƙuba ne.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Allah ya la'anci mata masu shasshawa da masu neman a yi musu da masu gyaran girar ido da masu yin wushirya domin ado, da masu

sauya halittar Allah mai girma da buwaya." Sai wannan magana ta Abdullahi ɗan Mas'ud ta je kunnen wata mata ana ce mata Ummu Yaƙub, sai nan da nan ta zo wurin Abdullahi ɗan Mas'ud ta ce masa: "Labari ya zo min kana faɗar kaza da kaza." Sai ya ce: "Me zai hana in la'anci wanda Manzon Allah (ﷺ) ya la'anta? Wannan ma ya zo a cikin Littafin Allah, watau Alƙur'ani." Sai ta ce: "Lalle ni fa na sha karanta Alƙur'ani daga bango zuwa bango amma ban taɓa samun wannan maganar a cikinsa ba." Sai ya ce: "Idan har kin taɓa karanta shi, to lalle kin taɓa cin karo da ita. Ba ki taɓa karanta faɗar Allah ba: "Abin da Manzon Allah (ﷺ) ya ba ku to ku karɓe shi, abin da kuma ya hana ku sai ku hanu"? Sai ta ce: "Lalle na gani." Sai ya ce: "To lalle Annabi (ﷺ) ya hana hakan." Sai ta ce masa: "To lalle ina zaton iyalanka ma suna aikata haka." Sai ya ce mata: "Ki je ki duba." Sai ta je amma ba ta ga abin da ta yi zato ba. Sai ta ce: "Ban ga komai ba." Sai ya ce: "Da ta kasance kamar yadda kika faɗa, to da ba ta sake zama da mu ba." [Bukhari #4886 da Muslim #2125].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yana daga cikin kyawawan tsare-tsaren Musulunci umarnin da ya bayar na a sarrafa wani kaso na dukiyar *'fai'u'* ga mutane mabuƙata ba mawadata ba kawai.

2. Falalar sahabbai waɗanda suka yi hijira zuwa Madina, watau Muhajirun, da samun shaida daga Allah a kan ikhlasinsu da gaskiyarsu da soyayyarsu gare shi da Manzonsa da son addinin Musulunci wanda suka sadaukar da rayuwarsu da dukiyoyinsu domin taimakonsa da yaɗa shi a duniya.

3. Falalar sahabbai mutanen Madina, watau Al-Ansar waɗanda suka shiga addinin Musulunci tun a farko suka kuma tanadar wa Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa wurin yin hijira, suka kuma ɗauki alƙawarin ba wa Manzon Allah (ﷺ) da addininsa kariya har inda ƙarfinsu ya ƙare, suka kuma cika wannan alƙawari, har addinin Allah ya yaɗu a hannunsu ya shiga garuruwa da al'ummu da dama.

4. Tabbatar da soyayyar da ke tsakanin sahabbai da al-Muhajirun da al-Ansar, saboda soyayyar Allah da Manzonsa ce ta haɗa su.

5. Tsarkin zukatan sahabbai mutanen Madina da rashin nuna son kansu, da yawan kyautarsu da karamcinsu.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fifita al-Muhajirun, watau sahabban da suka yiwo hijira zuwa Madina a kan al-Ansar, watau mutanen da suka karɓi baƙuncinsu, domin haka ne ya fara gabatar da su wajen ambato kafin ya ambaci mutanen Madina, sannan ya nuna an ba su abin da ba a ba wa mutanen Madina ba, domin su sun haɗa tsakanin yin hijira da kuma taimakon Musulunci.

7. Dangantaka ta imani ita ce sama da kowace irin dangantaka, domin ita ce ba ta yankewa har abada. Muminai duk inda suke masoya juna ne, masu yi wa juna kyakkyawar addu'a da kyakkyawan fata ne, ba sa sanya wani ƙulli ko hassada dangane da 'yan'uwansu muminai.

8. Yana daga cikin alamomin mumini na ƙwarai ya zamana yana son muminan magabata a cikin wannan al'umma, musamman sahabban Manzon Allah (ﷺ) da yawaita yi musu kyakkyawar addu'a da nema musu gafara da kawar da samun wata ƙiyayya ko ƙullata dangane da ɗaya daga cikinsu. Babu shakka wannan alama ce ta imani da nagartar bawa a wurin Allah.

9. Imamu Malik, Allah ya ji ƙan sa, ya kafa hujja da wannan ayar a kan cewa, duk wani ɗan Shi'a mai zagin sahabban Manzon Allah (ﷺ) ba shi da rabo a cikin dukiyar Musulmi, domin bai siffantu da ɗaya daga cikin

siffofin mutanen da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarta a ba wa wannan dukiya ba. [Dubi, *Ibn Kasir*, juzu'i na 8, shafi na 73].

10. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su roƙe shi kan ya cire musu duk wani ƙulli da hassada daga zukatansu game da muminai. Farkon waɗanda za su shiga a nan su ne sahabban Manzon Allah (ﷺ), domin su ne mafiya ɗaukaka a cikin muminai, sannan kuma a kansu ne ake magana. Duk wanda ya ƙi nema wa sahabbai gafarar Allah da yardarsa, to ya saɓa wa umarnin Allah a wannan ayar. Idan kuma ya ji wani ƙulli a zuciyarsa dangane da su, to ya sani cewa Shaiɗan ya yi nasara a kansa, ya jefa masa ƙiyayyar waliyyan Allah a zuciyarsa, waɗanda kuma su ne mafi alherin wannan al'umma bayan Annabi (ﷺ), don haka ya taɓe ya kuma buɗe wa kansa ƙofar zuwa wutar Jahannama matuƙar bai tuba ya koma ga Allah ba, ya roƙe shi ya cire masa ƙiyayyar bayinsa na ƙwarai daga zuciyarsa. To idan kuma al'amarinsa ya ƙara munana har ya kai ga zagin wasu daga cikinsu, to wannan ya miƙa ragamarsa ɗungurungum ga Shaiɗan ya tsunduma cikin hushin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). [Dubi, As-Shaukani, *Fatuhul Kadir*, juzu'i na 5, shafi na 240].

Suratul Hashr (8-10)

لِلْفُقَرَآءِ ٱلْمُهَٰجِرِينَ ٱلَّذِينَ أُخْرِجُوا۟ مِن دِيَٰرِهِمْ وَأَمْوَٰلِهِمْ يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنًا وَيَنصُرُونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّٰدِقُونَ ﴿٨﴾
وَٱلَّذِينَ تَبَوَّءُو ٱلدَّارَ وَٱلْإِيمَٰنَ مِن قَبْلِهِمْ يُحِبُّونَ مَنْ هَاجَرَ إِلَيْهِمْ وَلَا يَجِدُونَ فِى صُدُورِهِمْ حَاجَةً مِّمَّآ أُوتُوا۟ وَيُؤْثِرُونَ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ وَلَوْ كَانَ
بِهِمْ خَصَاصَةٌ ۚ وَمَن يُوقَ شُحَّ نَفْسِهِۦ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿٩﴾ وَٱلَّذِينَ جَآءُو مِنۢ بَعْدِهِمْ يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱغْفِرْ لَنَا وَلِإِخْوَٰنِنَا ٱلَّذِينَ سَبَقُونَا
بِٱلْإِيمَٰنِ وَلَا تَجْعَلْ فِى قُلُوبِنَا غِلًّا لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ رَبَّنَآ إِنَّكَ رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿١٠﴾

8. (Za a bayar da dukiyar) ga matalauta da suka yi hijira waɗanda aka fitar da su daga gidajensu da dukiyoyinsu don neman falala daga Allah da yardarsa, suna kuma taimakon (addinin) Allah da Manzonsa. Waɗannan su ne masu gaskiya.

9. Da kuma waɗanda suka tanadi gida (mutanen Madina) suka kuma (karɓi) imani gabaninsu (masu hijira), suna son waɗanda suka yi hijira zuwa gare su, ba sa samun wani ƙyashi a zukatansu game da abin da aka ba su (masu hijira), suna kuma fifita (masu hijira) a kan kawunansu, ko da kuwa suna da tsananin buƙata. Duk kuwa wanda aka kiyaye shi daga son kansa, to waɗannan su ne masu babban rabo.

10. Duk kuma waɗanda suka zo daga bayansu suna cewa: "Ya Ubangijinmu, Ka gafarta mana mu da 'yan'uwanmu waɗanda suka rigaye mu yin imani, kada kuma Ka sanya wata ƙullata a zukatanmu game da waɗanda suka yi imani, ya Ubangijinmu, lalle Kai Mai tausayawa ne, Mai jin ƙai."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ɓangare da za a ba wa dukiyar '*fai'u*', watau su ne matalauta masu hijira don Allah, waɗanda aka tilasta musu barin dukiyoyinsu da 'ya'yansu, suka yiwo ƙaura zuwa Madina wurin Manzon Allah (ﷺ) suna sanya tsammani Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu falalar wani arziki na duniya su kuma dace da samun yardarsa a lahira, suka kuma kasance tare da Manzon Allah (ﷺ) suna taimakon sa suna kuma taimakon addinin Allah ta hanyar jihadi don Allah. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, waɗanda suke da waɗannan siffofi su ne masu gaskiya waɗanda imani ya ratsa zukatansu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci mutanen Madina waɗanda suka karɓi Annabi (ﷺ) da sahabbansa masu hijira hannu bibbiyu, ya siffanta su da siffofi huɗu:
Ta ɗaya, sun zaɓi yin imani da Allah da Manzonsa (ﷺ).
Ta biyu, suna son waɗanda suka yiwo ƙaura daga Makka zuwa wajensu.

Ta uku, ba sa jin wani ƙyashi ko hassada ga muhajirai idan an ba su wani abu daga cikin dukiyar *‘fai’u*’ su ba a ba su ba.
Ta huɗu, suna fifita masu hijirar a kan kawunansu game da wani abin duniya ko da kuwa su suna da buƙata.

An karɓo daga Anas ɗan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kirawo mutanen Madina don ya ba su wani yanki daga dukiyar Bahraini, sai suka ce masa a’a, sai dai in zai ba wa ‘yan’uwansu mutanen Makka masu hijira. Annabi (ﷺ) ya ce musu: “To tun da haka ne sai dai su yi haƙuri har su haɗu da ni.” watau a ranar alƙiyama. [Bukhari #3794].

An karɓo daga Abu Hurairah (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mutanen Madina sun ce wa Manzon Allah (ﷺ): “Ka raba gonakin dabinanmu tsakaninmu da ‘yan’uwanmu masu hijira.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “A’a.” Sai suka ce wa masu hijira: “Ku ɗauke mana ɗawainiyar shayar da su, sai mu yi tarayya a kan amfaninsu.” Sai suka ce: “Mun ji, mun kuma bi.” [Bukhari #2326].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya kare shi daga tsananin kwaɗayin dukiya ga kansa, ya fito da ita ya bayar saboda Allah, to lalle irin waɗannan su ne masu samun babban rabo, domin za su dace da abin da ransu yake ƙauna, za su kuma kuɓuta daga duk abin da suke tsoro.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ku kiyayi zalunci, domin zalunci duffai ne a ranar alƙiyama, kuma ku kiyayi tsananin rowa, domin tsananin rowa ce ta hallaka waɗanda suka gabace ku, ta sanya su suka riƙa zubar da jinin junansu, suka kuma riƙa halatta cin mutuncin junansu.” [Muslim #2578].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin mutanen ƙwarai waɗanda suka zo bayan sahabban Manzon Allah (ﷺ) da cewa, su ne masu roƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gafarta musu tare da ‘yan’uwansu da suka rigaye su yin imani da Allah da Manzonsa, suke kuma roƙon sa da kada ya sanya wata ƙullata a zukatansu game da wani mumini, domin shi Allah mai tausayi ne ga bayinsa, kuma mai jin ƙai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rantsuwa a kan ƙarya da yaudara ɗabi’a ce ta munafukai.

2. Munafukai da Yahudawa mutane ne matsorata.

3. Kawance tsakanin Yahudawa da munafukai ƙawance ne na je-ka-na-yi-ka mai saurin gushewa idan an faɗa wani tsanani.

4. Yahudawa matsorata ne a fagen yaƙi; ba sa iya tunkarar Musulmi gaba-da-gaba a fagen yaƙi sai dai su noƙe a bayan manya-manyan gine-ginensu ko bayan makamansu na yaƙi.

5. Haɗin kan Yahudawa dodorido ne, domin saɓanin da yake tsakaninsu mai tsanani ne ainun.

6. Yahudawa mutane ne marasa lafiyayyen hankali, wanda hakan ya sanya su suka fifita ɓata a kan shiriya, suka kuma kasa samun kyakkyawan haɗin kai a tsakaninsu.

7. Duk sanda mutane ne suka ƙi gaskiya, to ba za su taɓa samun fahimtar juna ba ballantana su taɓuka wani abin kirki a tsakaninsu.

8. Shaiɗan yakan yi wa mutum shigo-shigo-ba-zurfi har ya ingiza shi cikin kafirci sannan kuma ya nesanta kansa da shi.

Suratul Hashr (11-17)

*أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ نَافَقُواْ يَقُولُونَ لِإِخۡوَٰنِهِمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ لَئِنۡ أُخۡرِجۡتُمۡ لَنَخۡرُجَنَّ مَعَكُمۡ وَلَا نُطِيعُ فِيكُمۡ أَحَدًا أَبَدٗا وَإِن قُوتِلۡتُمۡ لَنَنصُرَنَّكُمۡ وَٱللَّهُ يَشۡهَدُ إِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ١١ لَئِنۡ أُخۡرِجُواْ لَا يَخۡرُجُونَ مَعَهُمۡ وَلَئِن قُوتِلُواْ لَا يَنصُرُونَهُمۡ وَلَئِن نَّصَرُوهُمۡ لَيُوَلُّنَّ ٱلۡأَدۡبَٰرَ ثُمَّ لَا يُنصَرُونَ ١٢ لَأَنتُمۡ أَشَدُّ رَهۡبَةٗ فِي صُدُورِهِم مِّنَ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَفۡقَهُونَ ١٣ لَا يُقَٰتِلُونَكُمۡ جَمِيعًا إِلَّا فِي قُرٗى مُّحَصَّنَةٍ أَوۡ مِن وَرَآءِ جُدُرِۭۚ بَأۡسُهُم بَيۡنَهُمۡ شَدِيدٞۚ تَحۡسَبُهُمۡ جَمِيعٗا وَقُلُوبُهُمۡ شَتَّىٰۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَعۡقِلُونَ ١٤ كَمَثَلِ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ قَرِيبٗاۖ ذَاقُواْ وَبَالَ أَمۡرِهِمۡ وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١٥ كَمَثَلِ ٱلشَّيۡطَٰنِ إِذۡ قَالَ لِلۡإِنسَٰنِ ٱكۡفُرۡ فَلَمَّا كَفَرَ قَالَ إِنِّي بَرِيٓءٞ مِّنكَ إِنِّيٓ أَخَافُ ٱللَّهَ رَبَّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٦ فَكَانَ عَٰقِبَتَهُمَآ أَنَّهُمَا فِي ٱلنَّارِ خَٰلِدَيۡنِ فِيهَاۚ وَذَٰلِكَ جَزَٰٓؤُاْ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٧

11. Ba ka ga waɗanda suka yi munafunci suna ce wa ‘yan’uwansu waɗanda suka kafirta daga ma’abota littafi: “Tabbas idan aka fitar da ku, lalle za mu fita tare da ku, ba kuma za mu bi wani mutum game da ku ba har adaba, kuma idan aka yaƙe ku tabbas za mu taimake ku.” Allah kuma Ya san tabbas ƙarya suke yi.

12. Tabbas idan aka fitar da su ba za su fita tare da su ba, kuma tabbas idan aka yaƙe su ba za su taimake su ba, tabbas kuwa idan ma sun taimake su ɗin, lalle za su gudu su ba da baya, sannan kuma ba za a ba su nasara ba.

13. Tabbas ku suka fi tsoro a zukatansu fiye da Allah. Wannan kuwa saboda su mutane ne da ba sa fahimta.

14. Ba sa yaƙar ku a tare sai a cikin wasu alƙaryu katangaggu ko ta bayan katangu. Yaƙi a tsakaninsu mai tsanani ne. Za ka tsammaci kansu a haɗe yake, alhali zukatansu a rarrabe suke. Wannan kuwa saboda cewar su mutane ne da ba sa hankalta.

15. Sun yi kama da waɗanda suke a gabaninsu ba da daɗewa ba, sun ɗanɗani azabar al’amarinsu, suna kuma da (sakamakon) azaba mai raɗaɗi.

16. Sun yi kama da Shaiɗan lokacin da ya ce wa mutum: “Ka kafirta.” To yayin da ya kafirta sai ya ce: “Lalle ni ba ruwana da kai, lalle ni ina tsoron Allah Ubangijin talikai.”

17. Sai ƙarshen al’amarinsu ya kasance cewa su duka biyun masu dawwama ne cikin wuta. Wannan kuwa shi ne sakamakon azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) alƙawarin da munafukai suka yi wa Yahudawan Banun Nadhir yayin da suka riƙa zuga su suna tabbatar musu da cewa lalle su ci gaba da zama a gidajensu kada su yarda su fita, ko da kuwa Annabi ne ya umarce su da fita, suka rantse musu da Allah cewa ba za su bari a wulaƙanta su su kaɗai ba, domin har idan Musulmi za su kore su daga gidajensu, to su ma sun yi alƙawarin za su fita tare da su, don su nuna musu goyon baya, kuma ba za su saurari wani wanda zai hana su fita tare da su ba. Suka kuma rantse musu da Allah cewa lalle idan Musulmi suka yaƙe su, to tabbas za su taimaka musu wajen yaƙar Musulmi. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tona asirinsu ya bayyana wa Manzonsa cewa ya shaida lalle tabbas munafukai ƙarya suke ba za su taɓa fita tare da Yahudawa su bar gidajensu ba, kuma ba za su taɓa taimaka musu wajen yaƙar Musulmi ba.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, tabbas idan Musulmi suka fitar da Yahudawa daga gidajensu munafukai ba za su fita tare da su ba kamar yadda suke yi musu daɗin baki. Idan kuma Musulmi suka fara yaƙar Yahudawa, munafukai ba za su taimaka musu ba, kuma ko da za su fito da sunan taimakon su, to da zaran sun ga an fara yaƙi za su juya da baya su gudu su bar su, sannan kuma ba za a taɓa taimaka wa su munafukan ba, sai dai Allah ya wulaƙanta su su yi ta ganin ƙasƙanci.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙarfafa wa Musulmi gwiwa, ya kuma bayyana musu dalilin da zai sa munafukai ba za su taɓa taimaka wa Yahudawa a kan muminai a wajen yaƙi ba, saboda tabbas munafukai da Yahudawa sun fi tsoron muminai a zukatansu fiye da yadda ma suke tsoron Allah, ba kuma don wani abu ba sai don zamantowarsu mutane ne da ba sa fahimtar duk wata gaskiya da ake faɗa musu, domin da a ce suna ganewa to da kamata ya yi su ji tsoron Allah fiye da komai, domin shi ne yake ba wa muminai nasara a kansu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin tsoron Yahudawa ga muminai da cewa, ba za su taɓa yaƙar muminai a tare ba sai ta cikin garuruwa waɗanda suke kewaye da ganuwoyi, ko kuma ta bayan katangu, domin ba za su iya yin gaba-da-gaba da Musulmi ba saboda tsananin tsoronsu da raggwancinsu. Su kuma a tsakaninsu ba sa ga-maciji don tsananin gabar da take tsakaninsu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa idan ya gan su zai yi zaton kansu a haɗe yake babu wata ɓaraka a tsakaninsu, alhalin ba haka ne ba; zukatansu a rarrabe suke, saboda su mutane ne da ba sa hankalta, domin da suna aiki da hankalinsu da sun gane gaskiya ɗaya ce sun haɗa kansu a kanta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin irin yadda munafukai suke yaudarar Yahudawa da zaƙin baki da alƙawuran ƙarya, daga ƙarshe su kai su su baro. Ya bayyana cewa, sun yi kama da mushirikan Makka ne a ɗan wani lokaci baya ba da jimawa ba, watau lokacin yaƙin Badar, lokacin da suka ɗandani kuɗarsu a hannun Musulmi, aka kashe na kashewa aka kama na kamawa, sannan ga azaba can mai tsanani a lahira tana jiran su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, misalin Yahudawa waɗanda suke sauraron zaƙi bakin munafukai, kamar Shaiɗan ne lokacin da ya ƙawata wa mutum ya kafurta, to da zaran ya yarda ya kafirta ɗin sai Shaiɗan ya fito sarari yana faɗa masa cewa, shi fa ba ruwansa da kafircinsa, don shi yana jin tsoron azabar Allah. Karshen lamarin Shaiɗan kuwa da duk wanda ya bi umarninsa, shi ne su tabbata a wuta ranar alƙiyama, su kuma dawwama a cikinta har abada; wannan kuma shi ne sakamakon da yake jiran azzalumai masu ƙetare iyakokin Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dole ne bawa ya zamanto koyaushe mai yi wa kansa hisabi, mai binciken ayyukansa, inda duk ya ga wata tangarɗa ya gaggauta gyara ta, ya tuba zuwa ga Allah, ya nisanci duk abin da zai jawo masa hushinsa. Ya kuma dage wajen ayyukan alheri, ya nemi taimakon Ubangijinsa wajen kyautata ayyukansa da inganta su kamar yadda ya umarce shi da aikatawa.

2. Babbar asara ce ga bawa ya manta da umarnin mahaliccinsa, ya rafkana game da ambatonsa, ya mayar da hankalinsa a kan biyan buƙatun zuciyarsa da sha’awarsa.

3. Duk wanda ya watsar da shiriyar Allah da shari’arsa, to tun a nan duniya Allah zai rikita masa rayuwarsa, ya rasa gane maslahar kansa, domin zai yi rayuwa ne wanda bai san manufarta ba, bai kuma san alƙiblarsa ba, ya koma yana rayuwa irin ta dabbobi ba ta mutum da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karrama ba.

4. Ba za a taɓa samun daidaito tsakanin mumini da kafiri ba, ko mai bin Allah da Manzonsa da mai saɓa musu ba. A wurin Allah mumini mai bin sa shi ne mai rabauta da yardarsa.

Suratul Hashr (18-20)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَلۡتَنظُرۡ نَفۡسٞ مَّا قَدَّمَتۡ لِغَدٖۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ١٨ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ نَسُواْ ٱللَّهَ فَأَنسَىٰهُمۡ أَنفُسَهُمۡۚ أُوْلَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ١٩ لَا يَسۡتَوِيٓ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ وَأَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِۚ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ٢٠

18. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kiyaye dokokin Allah, kuma kowane rai ya dubi abin da ya gabatar don gobe (lahira); ku kuma kiyaye dokokin Allah. Lalle Allah Masanin abin da kuke aikatawa ne.

19. Kada kuma ku zama kamar waɗanda suka manta da Allah, sai Ya mantar da su kawunansu. Waɗannan su ne fasiƙai.

20. ‘Yan wuta da ‘yan Aljanna ba za su yi daidai ba. ‘Yan Aljanna su ne masu rabauta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira muminai ya umarce su da su kiyaye dokokinsa, su aikata abin da ya umarce su da shi, su kuma guji abin da ya hana su, sannan kowane mutum ya dubi kyakkyawan aikin da ya tanadar wa kansa domin ranar alƙiyama, watau su sanya tunanin wannan rana shi ne a zukatansu koyaushe, ya kuma sake jaddada musu umarnin su kiyaye dokokinsa sau-da-ƙafa, kada su bari wani abu na duniya ya ɗauke musu hankali, su kuma sani cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sane da duk abin da suke aikatawa mai kyau ko mummuna, kuma zai yi musu hisabi a kansa ranar alƙiyama.

An karɓo daga Jarir ɗan Abdullahi Al-Bajali (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana muna zaune a gaban Manzon Allah (ﷺ) da rana, sai ga wasu mutane sun zo masa, babu takalma a ƙafafunsu, suna kuma sanye da wasu yagaggun tufafi tsirara-tsirara, ɗauke da takubbansu, yawancinsu ko kuma dukkansu ‘yan ƙabilar Mudar ne. Da Annabi (ﷺ) ya ga irin tsananin talaucin da suke ciki sai fuskarsa ta canja, ya shiga gidansa ya fito, ya umarci Bilalu ya yi kiran salla ya yi iƙama. Annabi (ﷺ) ya yi wa mutane salla, sannan ya miƙe tsaye ya yi wa mutane jawabi, ya karanta faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): “Ya ku mutane, ku kiyaye dokokin Ubangijinku wanda ya halicce ku daga rai guɗa ɗaya....” [An-Nisa’i, aya ta 1]. Ya kuma karanta wannan ayar da ke cikin wannan Surar, sannan ya ce: “Kowane mutum ya bayar da sadaka daga dinarinsa ko dirhaminsa ko tufafinsa ko sa’in alkamarsa ko na dabinonsa.” Har ma ya ce: “Ko da da tsagin dabino ne....” [Muslim #1017].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja wa muminai kunne da cewa, kada su zama kamar waɗanda suka manta da Allah, watau suka yi watsi da aiki da umarninsa da guje wa haninsa, a kan haka sai Allah ya mantar da su kawunansu, suka ƙi yin aikin da zai tserar da su daga azabar Allah da hushinsa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, irin waɗannan mutane su ne fasiƙai waɗanda suka kangare wa ɗa’ar Allah da Manzonsa (ﷺ) suka zamanto ‘yan wuta.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ‘yan wuta da ‘yan Aljanna ba za su taɓa zama daidai ba, domin dole ne sakamakonsu ya sha bamban, kamar yadda a duniya ayyukansu suka sha bamban. ‘Yan Aljanna su ne masu rabauta a lahira, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ba su duk abin da suke so, zai kuma kuɓutar da su daga duk abin da suke ƙi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tunatar da mutum tsananin tasirin da Alƙur’ani zai yi, da abin a ce an saukar da shi a kan dutse. Wannan kuwa jan hankali ne ga mutum da cewa, shi ne ya kamata ya ji tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi matuƙar tasirantuwa da ayoyin Alƙur'ani da ake masa wa’azi da su, zuciyarsa komai ƙeƙashewarta ta yi laushi da sauraron wa’azinsa.

2. Tabbatar wa da Allah sunaye mafiya kyau masu ƙunshe da siffofi maɗaukaka.

3. Da a ce mushirikai sun fahimci sunayen Allah yadda ya kamata, da ba su yi tarayya da shi da komai ba, domin wanda ya siffantu da irin waɗannan siffofi ya fi ƙarfin a haɗa shi da kowane abu wajen bauta.

4. Tabbatar da tasbihin duk abubuwa da ke cikin sammai da ƙasa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka kangarewar wani daga cikin mutane ko aljannu ba zai cuci Allah da komai ba.

Suratul Hashr (21-24)
لَوۡ أَنزَلۡنَا هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ عَلَىٰ جَبَلٖ لَّرَأَيۡتَهُۥ خَٰشِعٗا مُّتَصَدِّعٗا مِّنۡ خَشۡيَةِ ٱللَّهِۚ وَتِلۡكَ ٱلۡأَمۡثَٰلُ نَضۡرِبُهَا لِلنَّاسِ لَعَلَّهُمۡ يَتَفَكَّرُونَ ٢١ هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِي
لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِۖ هُوَ ٱلرَّحۡمَٰنُ ٱلرَّحِيمُ ٢٢ هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِي لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡمَلِكُ ٱلۡقُدُّوسُ ٱلسَّلَٰمُ ٱلۡمُؤۡمِنُ ٱلۡمُهَيۡمِنُ ٱلۡعَزِيزُ
ٱلۡجَبَّارُ ٱلۡمُتَكَبِّرُۚ سُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٢٣ هُوَ ٱللَّهُ ٱلۡخَٰلِقُ ٱلۡبَارِئُ ٱلۡمُصَوِّرُۖ لَهُ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰۚ يُسَبِّحُ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ
ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٢٤

21. Da za Mu saukar da wannan Alƙur'ani ga wani dutse, da lalle ka gan shi yana mai ƙasƙantar da kai mai tsattsagewa don tsoron Allah. Waɗannan misalan Muna buga wa mutane su ne don su yi tunani.

22. Shi ne Allah wanda babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; Masanin ɓoye da sarari; kuma Shi ne Mai rahama, Mai jin ƙai.

23. Shi ne Allah wanda babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi; Shi ne Sarki, Mai tsarki, Amintacce, Mai amintarwa, Mai kula da komai, Mabuwayi, Mai tsananin ƙarfi; Mai nuna isa. Allah Ya tsarkaka daga abin da suke tara (Shi da shi).

24. Shi ne Allah Mahalicci, Mai ƙagawa Mai surantawa; Yana da sunaye mafiya kyau. Duk abin da yake cikin sammai da ƙasa yana tsarkake Shi; kuma Shi Mabuwayi ne, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) girman Alƙur'ani da tasirin wa'azuzzukansa, ba ga ɗan'adam da aljan ba kaɗai, har da daskararrun abubuwa, domin da a ce Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da shi ga dutse to da za a gan shi ya tsattsage saboda tsananin tsoron Allah, domin abin da yake cikin Alƙur'ani na wa'azi da tsoratarwa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan misalai ne yake buga wa mutane don su yi aiki da hankulansu, su wa'azantu da abin da ayoyin Alƙur'ani da wa'azozinsa masu ratsa jiki.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu daga cikin sunayensa mafiya kyau waɗanda suke ɗauke da siffofin kamala da isa, da cewa, shi ne Allah wanda babu wani abin bauta na gaskiya sai shi, masanin abin da yake ɓoye da na sarari, mai yalwar rahama a nan duniya ga kowa da kowa, mai jin ƙai a duniya da lahira ga bayinsa muminai. Shi ne Sarki mai cikakkiyar sarauta da mulkin komai a ƙasa da sama, tsarkakakke daga duk wani aibi, amintacce daga duk wata tawaya ko cuta, mai gaskata manzanninsa da ayoyin da yake ba su, mai kula da komai na ayyukan bayinsa, mabuwayi wanda babu mai iya karawa da shi, mai tsananin ƙarfi wanda ya fi ƙarfin kowane abu cikin halittarsa, mai nuna isa a kan kowa da komai, ya tsarkaka daga duk wani abu da mushirikai suke masa shirka da shi.
A ayar ƙarshe ta wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayyana cewa shi ne Allah mahaliccin komai, mai ƙagar halittar komai, mai suranta kamanninsu yadda ya ga dama, babu mai tarayya da shi a kan haka. Yana da sunaye mafiya kyau waɗanda suka ƙunshi siffofi mafiya ɗaukaka; duk abin da

yake cikin sammai da wanda yake ƙasa suna tsarkake shi daga duk wani aibi ko tawaya; shi ne mabuwayi wanda babu mai iya karawa da shi, mai hikima cikin halittarsa da shari'arsa da Kaddararsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin nuna soyayya da ƙauna ga maƙiyin Allah da Manzonsa (ﷺ).

2. Tsananin ƙiyayyar da mushirikai suka nuna wa Manzon Allah (ﷺ) da Musulman farko, har ta kai sun kore su daga gidajensu, sun raba su da dukiyoyinsu.

3. Kiyayyar kafirai ga Musulmi ba ta wani abu ce ba na duniya, ƙiyayya ce ta addini, don haka babu wani abu da Musulmi za su yi domin tunkarar wannan ƙiyayya tasu sai ƙanƙamewa kan da addininsu na gaskiya.

4. Babban burin maƙiya Musulmi shi ne su ga sun raba su da addininsu, sun kafirta kamar yadda su ma suka kafirta.

5. Bayyana wani asiri na Musulmi ga kafirai babban laifi ne a wurin Allah.

6. Duk yadda Musulmi zai nuna ƙaunarsa ga kafirai, ba fa za su taɓa ƙaunar sa ba har abada, domin ƙiyayyarsu gare shi ta yi zurfi matuƙa.

7. Duk sanda kafirai suka fi ƙarfin Musulmi, to ba za su taɓa ƙyale su su zauna lafiya ba, dole ne sai sun cutar da su da hannayensu ko da miyagun maganganunsu; zaman lafiyar Musulmi ɗaya ita ce su yi riƙo da sabubba na ƙarfi su kuma rungumi addininsu sosai.

8. Dangi da 'ya'ya ba za su amfani mutum ba a ranar alƙiyama, domin Allah zai raba tsakanin 'yan wuta da 'yan Aljanna kowanne ya tafi makomarsa, saboda haka ba za su amfani junansu da komai ba.

60-Suratul Mumtahana

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura an fi sanin ta da '*Suratul Mumtahana*', kamar yadda yake a cikin littattafan tafsiri da hadisi da kuma *masahifu*.
An kira ta da wannan suna ne saboda a cikin ayarta ta 10 an yi umarni da a jarraba mata muminai da suka yiwo hijira zuwa Madina don tabbatar da imaninsu.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya* ba tare da wani saɓani a tsakanin malamai ba.

3. Jerin Saukarta
Ita ce Sura ta tis'in da biyu (92) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratul Ma'ida*' kafin '*Suratun Nisa'i*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha uku ne (13), kuma masu tsawo.

5. Babban Jigonta:
Tana koyar da muminai tsantsanta biyayyarsu da soyayyarsu ga addinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Gargaɗin muminai game da ɗaukan mushirikai masoya tare da kafircinsu da tsananin gabarsu ga muminai.
• Bayanin cewa ɗaukar maƙiya Allah da Manzonsa a matsayin majiɓinta ɓata ne.
• Bayanin cewa mushirikai idan suka samu ɗama ba za su ƙyale muminai ba sai sun cutar da su da maganganunsu ko da ayyukansu. Dangantakar da take tsakaninsu da su ba za ta amfane su da komai ba saboda tsananin ƙiyayyarsu ga addininsu, kamar yadda ya faru tsakanin Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mahaifinsa da mutanensa.
• Kwantar wa muminai hankali da sa musu fatan cewa nan gaba Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya sanya soyayya a tsakaninsu da waɗannan maƙiyan nasu yayin da zai shiryar da su zuwa ga Musulunci, don haka gabarsu da su ba ta har abada ba ce.
• Umarni ga Musulmi da su kyautata mu'amalarsu ga kafiran da ba su yaƙe su saboda addininsu ba, ko su fitar da su daga gidajensu.
• Hukunce-hukunce na mata muminai da suka yiwo hijira zuwa Madina suka baro mazajensu da hana a mayar da su zuwa ga mazajensu kafirai bayan an tabbatar da gaskiyar imaninsu, amma kuma a mayar wa mazajensu abin da suka kashe wajen aurensu.
• Mubaya'ar mata muminai don gane irin riƙon su da suka yi wa shari'ar Musulunci.
• Haramta wa maza Musulmi auren mata mushirikai.

• Hana jiɓintar Yahudawa domin su da mushirikai ɗaya ne wajen nuna wa Musulmi ƙiyayya.

Suratul Mumtahana (1-3)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ عَدُوِّى وَعَدُوَّكُمْ أَوْلِيَآءَ تُلْقُونَ إِلَيْهِم بِٱلْمَوَدَّةِ وَقَدْ كَفَرُواْ بِمَا جَآءَكُم مِّنَ ٱلْحَقِّ يُخْرِجُونَ ٱلرَّسُولَ وَإِيَّاكُمْ أَن تُؤْمِنُواْ بِٱللَّهِ رَبِّكُمْ إِن كُنتُمْ خَرَجْتُمْ جِهَـٰدًا فِى سَبِيلِى وَٱبْتِغَآءَ مَرْضَاتِى ۚ تُسِرُّونَ إِلَيْهِم بِٱلْمَوَدَّةِ وَأَنَا۠ أَعْلَمُ بِمَآ أَخْفَيْتُمْ وَمَآ أَعْلَنتُمْ ۚ وَمَن يَفْعَلْهُ مِنكُمْ فَقَدْ ضَلَّ سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ﴿١﴾ إِن يَثْقَفُوكُمْ يَكُونُواْ لَكُمْ أَعْدَآءً وَيَبْسُطُوٓاْ إِلَيْكُمْ أَيْدِيَهُمْ وَأَلْسِنَتَهُم بِٱلسُّوٓءِ وَوَدُّواْ لَوْ تَكْفُرُونَ ﴿٢﴾ لَن تَنفَعَكُمْ أَرْحَامُكُمْ وَلَآ أَوْلَـٰدُكُمْ ۚ يَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ يَفْصِلُ بَيْنَكُمْ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ﴿٣﴾

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya ku waɗanda suka yi imani, ƙada ku riƙi maƙiyana kuma maƙiyanku masoya, kuna nuna musu soyayya, alhali kuwa sun kafirce wa abin da ya zo muku na gaskiya, suna fitar da Manzo har da ku kanku don kun yi imani da Allah Ubangijinku, idan har kun zamanto kun fito don yin jihadi saboda Ni da kuma neman yardata. Kuna ɓoye ƙaunarku gare su, alhali kuwa Ina sane da abin da kuka ɓoye da kuma abin da kuka bayyana. Duk kuwa wanda ya aikata haka daga cikinku, to haƙiƙa ya ɓace wa hanya madaidaiciya.

2. Idan suka samu nasara a kanku za su zama abokan gabanku, kuma za su miƙa hannayensu da harsunansu zuwa gare ku don munanawa, sun kuma yi burin ina ma da za ku kafirta.

3. Danginku da ‘ya’yanku ba za su amfana muku komai ba. A ranar alƙiyama kuma za a yi hukunci a tsakaninku da su. Kuma Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.,

Waɗannan ayoyi sun sauka ne game da labarin wani sahabi mai suna Haɗibu ɗan Abu Balta’ata, Shi ɗaya ne daga cikin sahabbai da suka yiwo hijira daga Makka zuwa Madina, ya kuma halarci yaƙin Badar tare da Manzon Allah (ﷺ). Ya baro ‘ya’yansa da dukiyarsa a Makka, kuma shi ba Baƙuraishe ne ba, don haka ba shi da wasu dangi a garin Makka da za su tsare masa ‘ya’yansa da dukiyarsa. Lokacin da Manzon Allah (ﷺ) ya ƙuduri niyyar zuwa Makka don yaƙar mutanenta bayan sun warware yarjejeniyar da aka ƙulla da su, sai Manzon Allah (ﷺ) ya sanar da wasu daga cikin sahabbai labarin abin da yake shirin aikatawa, daga cikinsu har da Haɗibu ɗan Abu Balta’ata. Sai Haɗibu (Allah ya ƙara masa yarda) ya rubuta wa Kuraishawa takarda yana ba su labarin abin da Manzon Allah yake shirya musu, ya danƙa takardar ga wata mace mushirika da ta zo Madina don ta kai musu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Manzonsa (ﷺ) abin da ake ciki, nan da nan ya umarci Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) da Zubairu (Allah ya ƙara masa yarda) da Miƙidadu (Allah ya ƙara masa yarda) da su bi bayan wannan matar su karɓo takardar da take hannunta. Haka kuwa aka yi, suka karɓo takardar suka dowa da ita ga Manzon Allah (ﷺ). Da Ma’aki (ﷺ) ya tambayi Haɗibu dalilinsa na aikata wannan ɗanyen aiki, shi kuma ya faɗa masa uzurinsa cewa, ba kafirci ko munafurci ko yi wa Musulunci zagon ƙasa ne ya sanya shi wannan aiki ba, a’a, ya yi haka ne da kyakkyawar niyya, domin ya san Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ba wa Manzonsa nasara a kan kafirai ko da kuwa sun sami labarin zuwansa domin yaƙar su, shi kuma yana buƙatar samun wani abu da zai yi wa Kuraishawa wanda zai faranta musu rai har su kula masa da ‘ya’yansa da dukiyarsa, kada su cutar da shi. Sai Annabi (ﷺ) ya karɓi hanzarinsa, Allah kuma ya yafe masa. [Dubi, Bukhari #3007 da Muslim #2494].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyi, yana kiran muminai waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa (ﷺ) da shari’ar da ya zo musu da ita cewa kada su riƙi duk wanda yake maƙiyansa kuma maƙiyansu a matsayin masoya har su nuna musu ƙauna, alhalin sun kafirce wa addinin da Manzonsa (ﷺ) ya zo musu da shi. Waɗannan ne fa suka kori Manzon Allah (ﷺ) har da su muminai

mabiyansa daga gidajensu a Makka, ba su damu da dangantakar da take tsakaninsu ko zumunci ba. Kuma sun yi musu haka ne ba don wani laifi da suka aikata ba, sai don kawai sun yi imani da Allah Ubangijinsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja kunnen muminai da kada su kuskura su riƙe su masoya matuƙar dai sun fito ne domin yin jihadi saboda shi da kuma neman yardarsa, ballantana ma su riƙa bayyana musu wani asiri na Musulmi don su nuna musu ƙauna, alhali kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sane da duk abin da za su ɓoye da wanda za su bayyana, domin babu abin da yake ɓuya a gare shi. Allah ya tabbatar musu da cewa duk wanda zai nuna ƙaunarsa da soyayyarsa ga kafirai, to lalle ya kauce wa hanyar Allah madaidaiciya ya rungumi ɓata da son zuciya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai tsananin ƙiyayyar da kafirai suke yi musu, da cewa, da abin a ce za su sami nasara a kan muminai ne, to lalle kuwa da za su fito da ƙiyayyar da ke cikin zukatansu a fili, za kuma su shimfiɗa hannayensu da nufin cutarwa, za kuma su saki kausasan harsunansu a kansu da zagi da cin mutunci, su kuma yi burin ina ma su ma muminan sun kafirce wa Allah da Manzonsa sun zama kamarsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa muminai cewa idan sun ɗauka cewa za su nuna wa kafirai ƙauna da soyayya saboda dangantaka ko dukiya, to su sani cewa danginsu da dukiyarsu ba za su amfana musu komai ba. A ranar alƙiyama Allah zai yi hukunci a tsakaninsu ya shigar da muminai daga cikinsu Aljanna, ya kuma shigar da mushirikai wuta, ashe kuwa ba wanda zai amfanar da wani daga cikinsu. Kuma Allah yana ganin duk abin da suke aikatawa, kuma zai yi wa kowa sakayya a kan aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin koyi da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka yi imani tare da shi, watau matarsa Saratu da ɗan ɗan'uwansa Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wajen bijire wa kafirci da kafirai da nuna fushi a kan kushe wa addinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kasance abin girmamawa a wajen Yahudawa da Nasara da Larabawa da al'ummu masu yawa, don haka buga misali da shi a kan wannan batu mai girma abu ne mai muhimmancin gaske.

2. Ba ya halatta ga mumini ya nema wa mushiriki gafarar Allah komai kusancinsa da shi.

3. Ba kowa ne zai iya koyi da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wajen ƙaurace wa kafirai da kafircinsu ba sai wanda yake ƙaunar samun alherin duniya da lahira.

4. Muminai sun roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da kada ya nufe su da zama fitina ga waɗanda suka kafirta, wannan ya ƙunshi ba wa kafirai nasara a kansu, abin da zai sanya su ƙara dulmiya cikin ɓatansu da kafircinsu domin zaton cewa a kan gaskiya suke, muminai kuma a kan ƙarya. Hakanan fitinar ta ƙunshi fitinuwar Musulmi game da addininsu yayin da aka ba wa kafirai galaba a kansu, wanda zai kai wasu su koma cikin ɓata ko su koma ga kafirci don guje wa fitinar kafirai gare su.

Suratul Mumtahana (4-6)

قَدْ كَانَتْ لَكُمْ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ فِيٓ إِبْرَٰهِيمَ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ إِذْ قَالُواْ لِقَوْمِهِمْ إِنَّا بُرَءَٰٓؤُاْ مِنكُمْ وَمِمَّا تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ كَفَرْنَا بِكُمْ وَبَدَا بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمُ ٱلْعَدَٰوَةُ وَٱلْبَغْضَآءُ أَبَدًا حَتَّىٰ تُؤْمِنُواْ بِٱللَّهِ وَحْدَهُۥٓ إِلَّا قَوْلَ إِبْرَٰهِيمَ لِأَبِيهِ لَأَسْتَغْفِرَنَّ لَكَ وَمَآ أَمْلِكُ لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن شَىْءٍ ۖ رَّبَّنَا عَلَيْكَ تَوَكَّلْنَا وَإِلَيْكَ أَنَبْنَا وَإِلَيْكَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٤﴾ رَبَّنَا لَا تَجْعَلْنَا فِتْنَةً لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ وَٱغْفِرْ لَنَا رَبَّنَآ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٥﴾ لَقَدْ كَانَ لَكُمْ فِيهِمْ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ لِّمَن كَانَ يَرْجُواْ ٱللَّهَ وَٱلْيَوْمَ ٱلْءَاخِرَ ۚ وَمَن يَتَوَلَّ فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ ﴿٦﴾

4. Haƙiƙa kyakkyawan abin koyi ya kasance a gare ku game da Ibrahimu da waɗanda suke tare da shi, lokacin da suka ce da mutanensu: “Lalle mu ba ruwanmu da ku, har ma da abin da kuke bauta wa ba Allah ba, mun kafirce muku, kuma gaba da ƙiyayya sun bayyana a tsakaninmu da ku har abada, har sai kun yi imani da Allah Shi kaɗai, in ban da faɗar Ibrahimu ga babansa cewa: ‘Lalle zan nema maka gafara, ba na kuma amfana maka komai game da (sakamakon) Allah’; ya Ubangijinmu gare Ka muka dogara, kuma zuwa wurinka muka mayar da lamuranmu, kuma makoma zuwa gare Ka ne.

5. “Ya Ubangijinmu, kada Ka sanya mu fitina ga waɗanda suka kafirta, Ka kuma gafarta mana ya Ubangijinmu; lalle Kai ne Mabuwayi, Mai hikima.”

6. Haƙiƙa abin koyi kyakkyawa ya kasance a gare ku game da su, ga duk wanda ya kasance yana kyakkyawan fatar haɗuwa da Allah da ranar lahira. Duk kuma wanda ya ba da baya, to lalle Allah Shi ne Mawadaci, Sha-Yabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar wa muminai cewa dangantaka ta jini ba za ta amfanar da su ba, domin imani da Allah shi ne kaɗai abin da zai ƙulla soyayya tsakanin muminai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su misali da ƙissar Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mabiyansa tare da mutanensa, inda ya tabbatar musu cewa, suna da kyakkyawan abin koyi da su lokacin da suke faɗa wa mutanensu kafirai cewa lalle su ba ruwansu da su da kuma gumakan da suke bauta wa ba Allah ba, suka bayyana musu ƙarara cewa, sun kafirce wa addininsu na ƙarya, kuma gaba da ƙiyayya sun bayyana a tsakaninsu ta har abada har sai lokacin da suka yi imani da Allah shi kaɗai, suka daina haɗa shi da komai. Don haka su ma Musulmi dole ne su nuna bara’arsu ga danginsu kafirai, watau ba ruwansu da su kamar yadda Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa suka yi. Amma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi togaciya game da alƙawarin da Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi na cewa zai roƙa wa mahaifinsa kafiri gafarar Allah. A nan kuma Musulmi ba za su yi koyi da shi ba, domin Annabi Ibrahimu ya faɗi haka ne kafin ya kai ga fitar da ran cewa mahaifinsa zai yi imani. Amma bayan ya tabbatar cewa mahaifin nasa maƙiyin Allah ne sai ya nesanta kansa daga gare shi ya fita daga sha’aninsa, kamar yadda Allah ya ambata a cikin *Suratut Tauba,* aya ta 114. Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana wa mahaifinsa cewa, ba zai kare masa komai na azabar Allah ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara nuna wa muminai cewa, suna da kyakkyawan abin koyi da Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da mutanensa lokacin da suke addu’a, suka mayar da al’amarinsu ga Ubangijinsu suna cewa, a gare shi kaɗai suka dogara cikin dukkan al’amuransu, kuma gare shi suke mayar da al’amuransu suna masu tuba, kuma suka tabbatar da cewa, zuwa gare shi ne makomarsu take.
Suka ci gaba da roƙon Allah a kan kada ya nufe su da zama fitina ga kafirai ta hanyar samun galabar kafirai a kansu har su riƙa cewa, da a kan gaskiya Musulmi suke da ba za su yi nasara a kansu ba. Suka kuma roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gafarta musu zunubansu, domin shi mabuwayi ne babu abin da yake gagararsa, mai hikima ne cikin halittarsa da shari’arsa da Kaddararsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tabbatar wa muminai cewa, wannan kyakkyawan abin koyi na Annabi Ibrahimu da mutanensa ba kowa ne zai iya koyi da su ba a kan haka sai wanda yake fatan samun alherin duniya da lahira daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Wanda kuwa ya bijire wa wannan kyakkyawan abin koyi, to Allah mawadaci ne ba ya buƙatar komai daga bayinsa, shi ne sha-yabo a cikin kowane hali.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zukatan bayi duka a hannun Allah suke yana jujjuya su yadda ya ga dama, don haka wajibi ne ga bawa ya dimanci roƙon Allah shiriya, don ya tabbatar da shi a kan imani.

2. Albishir ga Manzon Allah (ﷺ) da muminai da cewa wasu daga cikin maƙiyansu mushirikai za su musulunta a nan gaba. Haka kuwa ne ya faru, sai ga shi da yawa daga cikin mutanen Makka waɗanda suka riƙa nuna matsananciyar gaba ga Annabi (ﷺ) da Musulmi sun musulunta, kuma Musuluncinsu ya yi kyau, kamar irin su Abu Sufyan da ɗansa Mu'awiya da Khalid ɗan Walid da Ikrima ɗan Abu Jahl da sauransu da dama.

3. Bambancewa tsakanin hukuncin kafirai da suke yaƙar Musulmi da waɗanda ake zaune da su lafiya. Waɗanda suke yaƙar Musulmi da Musulunci suka hana Musulmi sakat, to waɗannan su ne aka yi umarni da kada a nuna musu wata fuska ta ƙauna ko taimako. Amma waɗanda ake zaune da su lafiya, to babu laifi a kyautata musu, musamman idan ya kasance akwai alaƙa ta jini a tsakani, kamar iyaye ko 'yan'uwa ko kuma alaƙa ta zamantakewa, to dole ne a kiyaye musu haƙƙoƙinsu da shari'a ta ba su, a kuma guji zaluntar su a cikin kowace irin mu'amala, a kuma yi musu adalci, domin Allah yana son masu adalci.

Suratul Mumtahana (7-9)

۞عَسَى ٱللَّهُ أَن يَجۡعَلَ بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَ ٱلَّذِينَ عَادَيۡتُم مِّنۡهُم مَّوَدَّةٗۚ وَٱللَّهُ قَدِيرٞۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٧ لَّا يَنۡهَىٰكُمُ ٱللَّهُ عَنِ ٱلَّذِينَ لَمۡ يُقَٰتِلُوكُمۡ فِي ٱلدِّينِ وَلَمۡ يُخۡرِجُوكُم مِّن دِيَٰرِكُمۡ أَن تَبَرُّوهُمۡ وَتُقۡسِطُوٓاْ إِلَيۡهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُقۡسِطِينَ ٨ إِنَّمَا يَنۡهَىٰكُمُ ٱللَّهُ عَنِ ٱلَّذِينَ قَٰتَلُوكُمۡ فِي ٱلدِّينِ وَأَخۡرَجُوكُم مِّن دِيَٰرِكُمۡ وَظَٰهَرُواْ عَلَىٰٓ إِخۡرَاجِكُمۡ أَن تَوَلَّوۡهُمۡۚ وَمَن يَتَوَلَّهُمۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٩

7. Zai yiwu Allah Ya sanya ƙauna tsakaninku da waɗanda kuka yi gaba da su. Allah kuwa Mai ikon (yin haka) ne. Allah kuma Mai gafara ne Mai jin ƙai.

8. Allah bai hana ku ba game da waɗanda ba su yaƙe ku don addini ba, ba su kuma fitar da ku daga gidajenku ba, kan ku kyautata musu, ku kuma yi musu adalci. Lalle Allah Yana son masu adalci.

9. Allah kawai Yana hana ku ne a kan ku ƙaunaci waɗanda suka yaƙe ku don addini, suka kuma fitar da ku daga gidajenku, suka kuma taimaka a kan fitar da ku. Duk kuwa wanda ya ƙaunace su, to waɗannan su ne azzalumai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa, umarnin da ya yi musu na yanke alaƙar soyayya tsakaninsu da kafirai ba yana nufin ba za su taɓa dawowa masoya ba har abada; akwai yiwuwar Allah ya sanya soyayya a tsakaninsu da abokan gabarsu kafirai, yayin da zai shiryar da su zuwa hanyar gaskiya, su rungumi Musulunci, sai a ƙarshe su zama 'yan'uwan juna a addini, domin Allah mai iko ne yana iya juyo zukatansu zuwa imani, kuma mai gafara ne ga bayinsa idan sun tuba sun bar kafirici, mai rahama ne gare su.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amr (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle zukatan 'yan'adam gaba ɗayansu suna tsakanin yatsu biyu daga Yatsun Allah mai rahama kamar zuciya ɗaya, yana jujjuya ta yadda ya ga dama." Sai kuma Manzon Allah (ﷺ) ya yi addu'a da cewa: "Ya Allah mai sarrafa zukata, ka sarrafa zukatanmu a kan ɗa'arka." [Muslim #2654].

An karɓo daga Amru ɗan Asi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Lalle na samu kaina a wani lokaci babu mutumin da nake ƙi kamar Manzon Allah (ﷺ), babu kuma wanda nake fatan in samu dama a kansa in kashe shi kamarsa. Da a ce na mutu a kan haka, da tabbas na zama ɗan wuta. Lokacin da Allah ya shigar da Musulunci cikin zuciyata, sai na zo wajen Manzon Allah (ﷺ) na ce masa: 'Shimfiɗa hannunka in yi maka mubaya'a'. Sai ya shifiɗa hannunsa na dama, amma sai ni kuma na danƙe hannuna". Sai ya ce: "Me ya same ka ne ya Amru?" Sai na ce: 'Ina so ne in sa sharaɗi'. Sai ya ce: "Wane sharaɗi kuma?". Sai na ce: 'A

gafarta mini zunubaina'. Sai ya ce: "Ba ka san cewa Musulunci yana rushe abin da ya gabace shi ba? Hijira ma tana rushe abin da ya gabace ta. Hajji ma yana rushe abin da ya gabace shi?" Amru ya ce: "Babu wani mutum da na ji ina so, ina kuma ganin girmansa kamar Manzon Allah (ﷺ), har ta kai ba na iya ƙura masa ido, don ganin girmansa da nake yi. Da a ce za a nemi in yi bayanin siffofinsa to ba zan iya ba, saboda ba na iya ƙura masa idanu. Idan zan mutu a wannan yanayi, to zan yi fatan in zama ɗan Aljanna…." [Muslim#121].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda), lokacin da Sumamatu ɗan Usal ya yi Kalmar Shahada ya karɓi Musulunci, sai ya ce wa Manzon Allah (ﷺ): "Ya Muhammd, a da babu wata fuska da na ƙi jinin in gani a bayan ƙasa kamar fuskarka, to lalle yanzu kuma an wayi gari bubu fuskar da nake so in gani kamar fuskarka. Na rantse da Allah a da can babu addinin da na tsana kamar addininka, yanzu kuwa an wayi gari babu wani addinin da nake so kamar addininka. Na rantse da Allah a da can babu garin da nake ƙi kamar garinka, amma yanzu an wayi gari babu garin da na fi so kamar garinka…" [Bukhari#4372 da Muslim#1764].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa muminai cewa hana su su nuna soyayya da ƙauna ga kafirai ba ya nufin kada su yi musu kyakkyawar mu’amala ko su kyautata musu. Allah bai hana su kyautata wa kafiran da ba su yaƙe su saboda Musuluncinsu ba, ba su kuma fitar da su daga gidajensu ba, suna iya kyautata musu, su yi musu adalci, su bai wa kowa haƙƙinsa yadda shari’a ta tsara, lalle Allah yana son masu yi wa kansu adalci su yi wa wasu.

An karɓo daga Asma’u ‘yar Abubakar, (Allah ya ƙara mata yarda), ta ce: Mahaifiyata wadda take mushirika ce, watau ba ta musulunta ba, ta zo wurina a Madina a daidai lokacin da Manzon Allah (ﷺ) ya yi sulhun zaman lafiya da Kuraishawa tana neman taimakona, sai na tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa zan iya sadar da zumuncin mahaifiyata? Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Na’am, ki sadar da zumuncin mahaifiyarki.” [Bukhari #2620 da Muslim #1003].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Akwai wani yaro Bayahude yana yi wa Manzon Allah (ﷺ) hidima, sai ya yi rashin lafiya, sai Manzon Allah (ﷺ) ya je duba shi, ya zauna daidai kansa ya ce masa: "Ka musulunta mana". Sai yaron ya kalli babansa da ke zaune a wurinsa, sai baban ya ce masa: "Yi wa baban Alƙasim biyayya". Sai nan take ya musulunta. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya fito yana cewa: "Na gode wa Allah da ya tserar da shi daga shiga wuta". [Bukhari#1356].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin kafiran da ya hana muminai su kyautata wa da cewa, su ne waɗanda suka yaƙe su saboda addininsu, suka kuma kore su daga gidajensu, ko suka taimaka wajen korarsu, to waɗannan bai halatta muminai su ƙulla soyayya da su ba, waɗanda kuwa suka kuskura suka ƙulla wata soyayya da su, to waɗannan sun zalunci kawunansu, domin sun jefa kawunansu cikin hallaka, don kuwa sun saɓa wa hanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ana yi wa mutane hukunci ne da imani bisa ga abin da ya bayyana daga gare su na zahiri, amma Allah ne ya san haƙiƙanin abin da zukata suka ƙunsa.

2. Matar da ta musulunta ta gudo zuwa wajen Musulmi, don ta tsira da imaninta, haramun ne a mayar da ita zuwa wajen ‘yan’uwanta kafirai, domin yin haka zai jefa imaninta da rayuwarta cikin haɗari.

3. Haramcin Musulmi ya auri mace kafira ko ya ci gaba da zaman aure da wadda ta yi ridda, sai wadda take bakitabiya ce, watau Bayahudiya ko Banasariya, wannan aurenta ya halatta bisa sharaɗin da aka ambata a cikin '*Suratul Ma'ida*' aya ta 5.

4. Haramcin mace Musulma ta auri kafiri ko ta ci gaba da zama da wanda ya kafirta.

Suratul Mumtahana (10-11)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا جَآءَكُمُ ٱلْمُؤْمِنَٰتُ مُهَٰجِرَٰتٍ فَٱمْتَحِنُوهُنَّ ۖ ٱللَّهُ أَعْلَمُ بِإِيمَٰنِهِنَّ ۖ فَإِنْ عَلِمْتُمُوهُنَّ مُؤْمِنَٰتٍ فَلَا تَرْجِعُوهُنَّ إِلَى ٱلْكُفَّارِ ۖ لَا هُنَّ حِلٌّ لَّهُمْ وَلَا هُمْ يَحِلُّونَ لَهُنَّ ۖ وَءَاتُوهُم مَّآ أَنفَقُواْ ۚ وَلَا جُنَاحَ عَلَيْكُمْ أَن تَنكِحُوهُنَّ إِذَآ ءَاتَيْتُمُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ ۚ وَلَا تُمْسِكُواْ بِعِصَمِ ٱلْكَوَافِرِ وَسْـَٔلُواْ مَآ أَنفَقْتُمْ وَلْيَسْـَٔلُواْ مَآ أَنفَقُواْ ۚ ذَٰلِكُمْ حُكْمُ ٱللَّهِ يَحْكُمُ بَيْنَكُمْ ۖ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿١٠﴾ وَإِن فَاتَكُمْ شَىْءٌ مِّنْ أَزْوَٰجِكُمْ إِلَى ٱلْكُفَّارِ فَعَاقَبْتُمْ فَاتُواْ ٱلَّذِينَ ذَهَبَتْ أَزْوَٰجُهُم مِّثْلَ مَآ أَنفَقُواْ ۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ ٱلَّذِىٓ أَنتُم بِهِۦ مُؤْمِنُونَ ﴿١١﴾

10. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan muminai mata sun zo muku suna masu yin hijira, sai ku jarraba su; Allah ne Ya fi sanin imaninsu; to idan kuka san cewa su muminai ne, to kada ku mayar da su wurin kafirai; su ba halal ba ne gare su (kafirai), su ma (kafiran) ba halal ba ne a gare su; kuma ku ba su abin da suka kashe. Kuma babu laifi a kanku ku aure su idan kun ba su sadakinsu. Kada kuma ku riƙe igiyar auren mata kafirai, ku tambayi abin da kuka kashe, su ma su tambayi abin da suka kashe. Wannan shi ne hukuncin Allah da Yake hukuntawa a tsakaninku. Allah kuma Masani ne, Mai hikima,

11. Idan wasu matanku sun guje muku zuwa ga kafirai, sai kuka yi yaƙi kuka samu galaba, to ku bai wa waɗanda matansu suka guje musu kamar abin da suka kashe. Ku kuma ku kiyaye dokokin Allah wanda kuke imani da Shi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin wasu hukunce-hukunce waɗanda suka danganci aure tsakanin muminai da mushirikai. Bayan Manzon Allah (ﷺ) ya yi sulhu da mushirikan Makka a shekara ta shida bayan hijira a Hudaibiyya, daga cikin abin da takardar sulhun ta ƙunsa akwai cewa, duk wanda zai gudu daga wajen Musulmi zuwa wurin mushirikai, to ba za su mayar musu da shi ba, amma kuma duk wanda zai gudu daga cikin mushirikai zuwa wurin Musulmi, to dole su dawo musu da shi. Annabi (ﷺ) ya sa hannu a kan wannan yarjejeniya, ya mayar musu da duk wani namiji da ya gudo daga wajensu.

Sai dai su mata Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya togace su daga wannan sharaɗin, saboda girman ɓarnar da za ta faru idan an mayar da su wurin kafirai bayan sun gudo suna muminai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kira ga muminai ya bayyana musu cewa, idan muminai mata masu hijira suka zo musu, watau waɗanda suka gudo daga ƙasar kafirai zuwa ƙasar Musulmi, to su jarraba gaskiyar imaninsu. Allah dai shi ne mafi sanin imaninsu, domin shi ne ya san abin da yake ɓoye a cikin zukata. To idan sun bincika sun gane su muminai ne da gaske, to kada su mayar da su ga mazajensu kafirai, domin ba ya halatta ga muminai mata su auri mazaje kafirai, su ma kafirai maza ba ya halatta su auri mata muminai. To idan Musulmi suka riƙe matan kafirai waɗanda suka gudo suna masu imani, to sai su mayar wa da mazajensu sakadin da suka kashe wajen aurensu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa muminai cewa babu laifi su auri waɗannan matan bayan sun gama iddarsu sun kuma biya sadakinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana mumini zama da matarsa kafira ko wadda ta yi ridda ta bar Musulunci, domin kafircinta ya yanke igiyar aure da ke tsakaninsu. Sannan duk matan da suka yi ridda suka gudu zuwa wajen kafirai, to su nemi kafirai su biya su abin da suka kashe na sadakin aurensu, su ma kafiran su nemi Musulmi su biya su sadakin matansu da suka musulunta suka gudo wajen Musulmi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, wannan abin da aka ambata na mayar wa da kowa sadakinsa shi ne hukuncinsa da ya yanke a tsakaninsu, domin shi masanin halayen bayinsa ne da ayyukansu, babu abin da yake ɓuya gare shi, kuma mai hikima ne cikin duka ayyukansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, idan aka ƙaddara cewa wasu daga cikin matan Musulmi sun yi ridda sun gudu wajen kafirai suka nemi kafirai su dawo musu da abin da suka kashe wajen aurensu amma suka ƙi, to idan an samu wata ganima ta yaƙi daga waɗannan kafiran, to sai a ba wa mazajen da matansu suka yi ridda suka gudu zuwa kafirai gwargwadon abin da suka kashe wajen aurensu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su kiyaye dokokin Allah wanda suka yi imani da shi, su bi umarninsa su kuma guje wa haninsa.

An karɓo daga Al-Miswaru ɗan Makhrama (Allah ya ƙara masa yarda) da Marwana ɗan Hakam suka ce: Yayin da Manzon Allah (ﷺ) ya rubuta takardar sulhu tare da Suhailu ɗan Amru a ranar Hudaibiyya, yana daga cikin abin da Suhailu ya sharɗanta cewa: "Duk wani wanda zai zo wajenka daga cikinmu, ko da kuwa yana kan addininka, to za ka dawo mana da shi". A nan ne Manzon Allah (ﷺ) ya mayar da Abu Jandal ɗan Suhailu. Duk kuma wani namiji da ya zo wa Manzon Allah a wannan lokaci sai da ya mayar da shi ko da kuwa Musulmi ne. Sannan sai mata muminai masu hijira suka zo. Ummu Kulsum ‘yar Uƙbata ɗan Abu Mu’aiɗ tana cikin waɗanda suka gudu zuwa ga Manzon Allah (ﷺ) tana budurwa ‘yar ƙarama, sai danginta suka zo suna neman Manzon Allah (ﷺ) ya mayar musu da ita, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar. [Bukhari #2711].

An karɓo daga Al-Miswaru ɗan Makhrama (Allah ya ƙara masa yarda) da Marwana ɗan Hakam suka ce: Lokacin da Manzon Allah (ﷺ) ya ƙulla yarjejeniya da Kuraishawa a ranar Hudaibiyya, sai wasu mata muminai suka je masa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar har zuwa inda yake cewa: (Kuma babu laifi a kanku idan kun aure su....) Sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) a wannan lokacin ya saki wasu mata biyu waɗanda suke kan shirka, watau ba su musulunta ba. [Bukhari #2731].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yi wa shugaba mubaya’a a kan bin Allah da dokokinsa da biyayya ga shugaba cikin abin da bai saɓa wa Allah ba.

2. Halaccin mubaya’ar mata ga shugaba a kan ɗa’ar Allah da kauce wa saɓonsa ba tare da kama hannayensu ba.

3. Mata suna tarayya da maza wajen bin hukunce-hukuncen shari’a babu bambanci sai a inda Allah da Manzonsa suka bambanta tsakaninsu.

4. Haramcin shirka da sata da zina da kashe ‘ya’ya da maƙala wa miji ɗan da ba nasa ba.

Suratul Mumtahana (12)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ إِذَا جَآءَكَ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتُ يُبَايِعۡنَكَ عَلَىٰٓ أَن لَّا يُشۡرِكۡنَ بِٱللَّهِ شَيۡـٔٗا وَلَا يَسۡرِقۡنَ وَلَا يَزۡنِينَ وَلَا يَقۡتُلۡنَ أَوۡلَٰدَهُنَّ وَلَا يَأۡتِينَ بِبُهۡتَٰنٖ يَفۡتَرِينَهُۥ بَيۡنَ أَيۡدِيهِنَّ وَأَرۡجُلِهِنَّ وَلَا يَعۡصِينَكَ فِي مَعۡرُوفٖ فَبَايِعۡهُنَّ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لَهُنَّ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١٢

12. Ya kai wannan Annabi, idan muminai mata suka zo maka suna yi maka mubaya’a a kan ba za su yi shirka da Allah ba, kuma ba za su yi sata ba, ba kuma za su yi zina ba, kuma ba za su kashe ‘ya’yansu ba, kuma ba za su zo da wani ƙage ba wanda za su ƙirƙira (game da ɗan da suka haifa) a tsakanin hannayensu da

ƙafafuwansu, kuma ba za su saɓa maka ba game da wani aiki na kirki, to sai ka yi musu mubaya'a, ka kuma nema musu gafarar Allah. Lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A wannan aya Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) sigar da zai yi wa mata mubaya'a a kanta idan sun zo masa don yi masa mubaya'a, kamar yadda ya faru lokacin buɗe Makka. Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya yi musu mubaya'a a kan abubuwa shida:
Na farko, ba za su haɗa Allah da komai ba, za su bauta masa shi kaɗai.
Na biyu, ba za su yi sata ba.
Na uku, ba za su yi zina ba, kamar yadda abin ya watsu a zamanin jahiliyya a tsakanin mata masu zaman kansu da waɗanda suke riƙar su a matsayin dadiro.
Na huɗu, ba za su kashe 'ya'yansu ba, kamar yadda kashe 'ya'ya mata ya zama ruwan dare a tsakanin kafiran Larabawa a zamanin jahiliyya.
Na biyar, ba za su zo da wani ƙage ba na 'ya'yan da za su haifa su maƙala wa mazajen da ba su ne iyayensu ba, kamar yadda mace a jahiliyya za ta yi zina da mazaje da yawa idan ta haihu sai ta zaɓi ɗaya daga cikinsu ta maƙala masa ɗan; ko tana matar aure sai ta haifi ɗan zina sannan ta jingina wa mijinta.
Na shida, ba za su saɓa wa Manzon Allah (ﷺ) game da wani aikin alheri ba, kamar idan ya hana su koke-koken mutuwa ko aske kai ko yaga tufafi saboda faruwar wata musiba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) cewa, idan sun yarda da waɗannan sharuɗɗa to ya yi musu mubaya'a, ya kuma nema musu gafarar Allah game da zunubbansu bayan ya gama mubaya'a da su, lalle Allah mai gafara ne ga duk wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai jin ƙai ne a gare su.

An karɓo daga A'isha, (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance ya riƙa jarraba mata muminai da suka yiwo hijira da wannan, duk wadda ta yarda da wannan sharaɗin sai ya ce mata: "Na yi miki mubaya'a" da magana. Na rantse da Allah, hannunsa bai taɓa hannun wata mace ba yayin yi mata mubaya'a. Bai yi musu mubaya'a ba sai da faɗarsa: "Na yi miki mubaya'a a kan haka." [Bukhari #2713 da Muslim #1866].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na halarci sallar idin Ramadana tare da Manzon Allah (ﷺ), sai ya gangaro ya zo inda mata suke sai ya karanta musu wannan ayar har zuwa ƙarshenta, sannan ya ce musu: "Shin kuna kan wannan ne?" Sai wata mata ta ce: "Na'am." [Bukhari #979 da Muslim #4895].

An karɓo daga Umaima 'yar Ruƙaiƙa (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Na zo wurin Annabi (ﷺ) tare da mata don yi masa mubaya'a, sai ya sharɗanta mana abin da ya zo a cikin Alƙur'ani cewa ba za mu haɗa Allah da komai ba, har ya kai inda Allah yake cewa: (Kuma ba za su saɓa maka ba game da wani aiki na kirki...) sai ya ce: "Cikin abin da za ku iya wanda bai fi ƙarfinku ba." Sai muka ce: "Allah da Manzonsa sun fi tausaya mana fiye da kawunanmu. Ya Manzon Allah, shin ba ka yi hannu da mu ba?" Sai ya ce: "Ni ba na hannu da mata, kawai maganata ga mace ɗari daidai take da maganata ga mace ɗaya." [Ahmad #27010 da Tirmizi #1687 da Nasa'i #4181 da Ibn Maja #2874].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin haɗa kai da Yahudawa da nuna musu soyayya.

2. Tabbatar wa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) siffar hushi kamar yadda ya dace da shi.

3. Kafirai da suka mutu sun ɗebe ƙauna daga samun wani kyakkyawan sakamako a lahira tun kafin tashin alƙiyama, saboda mummunan sakamakon da aka nuna musu.

Suratul Mumtahana (13)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَوَلَّوۡاْ قَوۡمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ قَدۡ يَئِسُواْ مِنَ ٱلۡأٓخِرَةِ كَمَا يَئِسَ ٱلۡكُفَّارُ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلۡقُبُورِ ١٣

13. Ya ku waɗanda kuka yi imani, kada ku jiɓinci mutanen da Allah ya yi fushi da su, haƙiƙa sun ɗebe ƙauna daga lahira kamar yadda kafirai suka ɗebe ƙauna daga na ƙabarurruka.

A wannan aya ta ƙarshen Sura Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira muminai ya ja kunnensu da cewa kada su kuskura su jiɓinci mutanen da ya yi fushi da su, watau Yahudawa waɗanda, saboda yawan saɓonsu da kafircinsu har Allah ya yi hushi da su, sun ɗebe ƙauna daga samun wani rabo a lahira, domin ba rashin sanin gaskiya ba ne ya jefa su cikin kafirci, sun san gaskiya sarai amma sai suka take ta, don haka ba sa ran samun wani kyakkyawan sakamako daga Allah a ranar lahira, kamar yadda kafirai waɗanda suka mutu aka binne su a ƙaburburansu, aka nuna musu makomarsu a wutar Jahannama suka fitar da tsammanin samun kuɓuta a ranar alƙiyama.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da girman Allah da isar Kudurarsa, domin duk wani abu a ƙasa ko a sama yana yi masa tasbihi tare da tsarkake shi.

2. Wajibi ga mumini maganarsa ta riƙa dacewa da aikinsa, ya guji cika baki ko faɗa babu cikawa.

3. Haɗin kan Musulmi a kan gaskiya da taimakon addinin Allah, shi ne kaɗai abin da zai ƙara musu ƙarfi da kwarjini a wurin maƙiyansa, shi ne kuma zai sanya Allah ya so su.

4. Tabbatar wa Allah siffar 'So' kamar yadda ya dace da ɗaukakarsa da girman matsayinsa, don haka Allah yana son bayinsa nagari su ma suna son sa.



61-Suratus Saff

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da suna *'Suratus Saffi*' kamar yadda ya zo a littattafan hadisai da tafsirai.
An kuma kira ta da wannan suna ne saboda lafazin '*Saffu*', watau 'sahu' da ya zo cikinta a aya ta 4.
An ruwaito cewa Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya kira ta da suna '*Suratul Hawariyyin*' saboda lafazin '*Al-Hawariyyin*' da ya zo a cikinta, a aya ta 14.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai sun ce Sura ce *Madaniyya*, watau an saukar da ita bayan hijirar Manzon Allah (ﷺ) zuwa Madina. Amma wani ƙauli ya inganta daga Abdullahi ɗan Abbas inda yake cewa, Sura ce *Makiyya*. Sai dai mafi yawancin ruwayar da aka yiwo daga gare shi yana cewa ne Sura ce *Madaniyya.* Wannan kuma shi ne ya fi inganci.

3. Jerin Saukarta
Ita ce Sura ta ɗari da takwas (108) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratut Tagabun*' kafin '*Suratul Fat'h'.*

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta goma sha huɗu ne (14) babu wani sabani.

5. Sababin Saukarta
An karƀo daga Abdullahi ɗan Salam (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Mun zauna, mu sahabban Manzon Allah (ﷺ) muna tattaunawa sai muka ce: "Da a ce mun san aikin da ya fi kowane aiki kusantarwa zuwa ga Allah da mun aikata shi. Sai Allah ya saukar da wannan Surar. Annabi (ﷺ) ya karanta mana ita kamar haka ɗin nan. [Ahmad #23788 da 23789 da Tirmizi #3595 da Ibn Hibban #4594].

6. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne zaburar da muminai a kan su tashi su yi jihadi su taimaki addinin Allah.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Jan kunne da gargaɗi game da saba alƙawarin da mutum ya ɗaukar wa kansa.
• Kwaɗaitarwa a kan yin jihadi don Allah da jajircewa a kansa da gaskiyar imani da tsayawa kyam wajen taimakon addini.
• Koyi da mutane masu gaskiya, kamar Hawariyawa almajiran Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
• Gargaɗi game da cutar da Annabi (ﷺ) kamar yadda Yahudawa irin Ka'abu ɗan Ashrafu suke yi masa da bayar da misali da irin abin da Yahudawa suka yi wa Annabi Musa da Annabi Isa .

• Yi wa waɗanda suka yi imani na gaskiya suka kuma yi jihadi don Allah alƙawarin kyakkyawan sakamako a lahira da samun nasara a duniya.

Suratus Saff (1-4)

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لِمَ تَقُولُونَ مَا لَا تَفۡعَلُونَ ٢ كَبُرَ مَقۡتًا عِندَ ٱللَّهِ أَن تَقُولُواْ مَا لَا تَفۡعَلُونَ ٣ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلَّذِينَ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِهِۦ صَفّٗا كَأَنَّهُم بُنۡيَٰنٞ مَّرۡصُوصٞ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa ya yi tasbihi ga Allah; Shi kuma Mabuwayi ne, Mai hikima.

2. Ya ku waɗanda suka yi imani, don me kuke faɗar abin da ba kwa aikatawa?

3. Ya isa babban abin ƙi a wurin Allah, ku riƙa faɗin abin da ba kwa aikatawa.

4. Lalle Allah Yana son waɗanda suke yin yaƙi dominsa sahu-sahu kai ka ce su gini ne wanda yake ɗamfare da juna.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da bayanin girmansa da ɗaukakarsa da cewa, duk abin da yake sammai da wanda yake ƙasa sun tsarkake shi daga duk wani abu wanda bai dace da shi ba, kuma shi ne mabuwayi wanda babu abin da yake gagarar sa, mai hikima ne cikin halittarsa da ƙaddararsa da shari'arsa. Sai kuma ya kira muminai ya tsawatar musu game da faɗin maganar da ba za su yi aiki da ita ba, domin ba abu ne mai kyau ga mumini ba ya riƙa faɗa ba cikawa, domin wannan wani babban abin ƙi ne a wurin Allah bawansa ya faɗi abin da ba zai yi aiki da shi ba, ko ya faɗi abin da bai aikata ba ya ce ya aikata, dole ne ya zamanto mai gaskiya tare da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Kafin a wajabta wa Musulmi yin jihadi wasu daga cikin muminai sun riƙa cewa: Ina ma a ce Allah ya nuna mana wani aiki na kirki da ya fi so, da mun aikata shi? Sai Allah ya sanar da Manzonsa cewa, mafi soyuwar ayyuka a wajensa shi ne imani da Allah imanin da babu shakka a cikinsa da yaƙar masu saɓa masa waɗanda suka ƙi yin imani da shi, suka ƙi yarda da shi. To lokacin da umarni da yin jihadi ya sauko, sai wasu daga cikin muminai abin bai yi musu daɗi ba; umarnin ya yi musu nauyi, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce musu: "Don me kuke faɗar abin da ba kwa aikatawa?" [Ibn Jarir, Tafsir, juzu'i na 23, shafi na 606-607].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Alamar munafuki uku ce; idan ya yi magana sai ya yi ƙarya; idan kuma an yi alƙawari da shi sai ya saɓa; idan kuma aka amince masa sai ya ci amana." [Bukhari #33 da Muslim #59].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yabi masu yaƙi don ɗaukaka addininsa, da cewa, lalle yana son muminai masu fita suna yaƙi saboda Allah sahu-sahu a kan dawakansu ko tafe da ƙafafunsu, kamar gini wanda sashinsa yake manne da sashe, watau a cikin tsari da haɗin kai ba tare da sun bar wani giɓi a tsakaninsu ba.

An karɓo daga Muɗarrif ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na sami labarin wani hadisi na Abu Zarri sai na so mu haɗu don in tambaye shi, sai muka haɗu wata rana sai na ce masa: Na sami labarin wani hadisi naka nake son haɗuwa da kai don in tambaye ka, sai ya ce: To ga shi mun haɗu, tambayi abin

da kake so. Sai na ce: Na sami labarin cewa kai kana cewa: Ka ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: “Mutum uku Allah yana son su mutum uku kuma Allah yana ƙin su.” Sai ya ce: Haka ne. Kuma ba na zaton zan yi wa badaɗayina Muhammad (ﷺ) ƙarya. Ya faɗi haka har sau uku. Sai na ce masa: Su wane ne ukun da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake so? Sai ya ce: Mutumin da ya fita yaƙi domin Allah, ya haɗu da abokin gaba yana mai jihadi mai neman lada, ya yi yaƙi har aka kashe shi. Kuma wannan abu ne da za ku same shi a Littafin Allah, inda yake cewa: “Lalle Allah yana son masu yaƙi domin addininsa sahu-sahu.”; da mutumin da maƙocinsa yake cutar da shi shi kuma yana ta haƙuri game da cutarwarsa, yana neman lada a wurin Allah har lokacin da Allah ya isar masa shi ta hanyar mutuwa ko rayuwa; da mutumin da yake tafiya cikin ƙungiya ta mutane, sai sun yi tafiya har sun gaji barci ko gyangyaɗi ya fara kama su sai su ya da zango a ƙarshen dare, shi kuma sai ya tashi ya nufi wajen alwalarsa da sallarsa. To sai na ce: Su wane ne kuma mutum ukun da Allah yake ƙi? Sai ya ce: Mai fariya mai taƙama, kuma za ku samu wannan a Littafin Allah, inda yake cewa: “Lalle Allah ba ya so mai taƙama mai fariya.” [Luƙman: 18]; da kuma marowaci mai gori; da ɗan kasuwa mai yawan rantsuwa. [Ahmad #21530 da Tirmizi #2568].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa bawa hanyar alheri da ta sharri, to idan bawa ya zaɓi ɓata bai tuba ba, sai Allah ya yi masa uƙuba da ƙara masa karkata da ɓata.

2. Rashin yi wa Manzon Allah (ﷺ) biyayya da aiki da umarninsa, yakan jefa bawa cikin ɓata da hallaka.

3. Dukkan manzannin Allah da suka gabata sun yi albishir da zuwan Manzon Allah (ﷺ) wanda hakan yana nuna gaskiyar annabcinsa (ﷺ) da ingancin abin da ya zo da shi.

Suratus Saff (5-6)

وَإِذْ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦ يَٰقَوْمِ لِمَ تُؤْذُونَنِى وَقَد تَّعْلَمُونَ أَنِّى رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُمْ ۖ فَلَمَّا زَاغُوٓا۟ أَزَاغَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُمْ ۚ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ۝٥ وَإِذْ قَالَ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ يَٰبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ إِنِّى رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُم مُّصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَىَّ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَمُبَشِّرًۢا بِرَسُولٍ يَأْتِى مِنۢ بَعْدِى ٱسْمُهُۥٓ أَحْمَدُ ۖ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ قَالُوا۟ هَٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ ۝٦

5. Kuma (ka tuna) lokacin da Musa ya ce da mutanensa: “Ya ku mutanena, don me kuke cuta ta, alhali kuma kun san cewa lalle ni Manzon Allah ne zuwa gare ku?” To lokacin da suka kauce sai Allah ya kautar da zukatansu. Allah kuma ba ya shiryar da mutane fasiƙai.

6. Kuma (ka tuna) lokacin da Isa ɗan Maryamu ya ce: “Ya ku ‘ya’yan Isra’ila, lalle ni Manzon Allah ne zuwa gare ku, mai gaskata abin da yake gabanina na Attaura, kuma mai albishir da wani manzo da zai zo bayana, sunansa Ahmadu.” To lokacin da ya zo musu da (ayoyi) bayyanannu sai suka ce: “Wannan sihiri ne mabayyani.”

A waɗannan ayoyi kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi muminai ne ya ja musu kunne ta hanyar nuna musu mummunan halin Yahudawa ga Annabin da Allah ya aiko musu, watau Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) don ya shiryar da su ya kuma kuɓutar da su daga zaluncin Fir’auna da mutanensa, amma sai suka riƙa cutar da shi da maganganunsu da ayyukansu, har ya riƙa kiran su yana tambayar su cewa, me ya sa suke cutar da shi, alhalin sun san cewa shi Manzon Allah ne zuwa gare su? Watau wanda ya kamata su fi kula da haƙƙinsa da girmansa da kiyaye masa mutuncinsa, saboda shi manzo ne ya fi kowa kyautatawa ga mutanensa don girman abin da ya zo musu da shi. To amma Banu Isra’ila sai suka kauce wa tafarki madaidaici, suka yi watsi da abin da Annabi Musa (Amincin Allah ya

tabbata a gare shi) ya zo musu da shi, don haka sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kautar da zukatansu daga karɓar gaskiya da aiki da ita, saboda wannan shi ne zaɓinsu; Allah kuma ba ya shiryar da mutanen da suka tabbata fasiƙai masu bijire wa manzannin Allah waɗanda suka zo musu da shiriya.
Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa muminai labarin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), lokacin da ya kirawo mutanensa Banu Isra'ila ya tabbatar musu cewa, shi Manzon Allah ne zuwa gare su, ya zo musu yana mai gaskata littafin Attaura da ya gabace shi, don haka ba shi ne farkon manzo a cikinsu ba, sannan ba shi zai zama manzo na ƙarshe da Allah zai aiko a bayan ƙasa ba, don haka ne ma yake yi musu albishir da wani manzo da zai zo a bayansa mai suna Ahmadu, watau Annabi Muhammadu (ﷺ).

An karɓo daga Ubadatu ɗan Samit (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An ce: Ya Manzon Allah, ba mu labarin kanka, sai ya ce: "Ni ne addu'ar babana Ibrahim, kuma ƙarshen wanda ya yi albishir da ni shi ne Isa ɗan Maryam (Amincin Allah ya tabbata a gare shi)." [Ibni Asakir, *Tarikhu Dimashaƙ*, juzu'i na 3, shafi na 393. Dubi, Albani, *As-Silsilatus Sahiha*, #1546].

An karɓo daga Jubairu ɗan Muɗ'im (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ina da sunaye biyar: Ni ne Muhammad; ni ne Al-Mahi wanda Allah yake share kafirci da ni; ni ne Al-Hashiru, wanda Allah yake tattaro mutane a bayana (ranar alƙiyama); ni ne Al-Aƙibu." [Bukhari #4896 da Muslim #2354].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk da kasancewar Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo wa mutanensa da hujjoji bayyanannu masu tabbatar da gaskiyarsa, amma sai mutanensa suka ƙaryata shi suka ce abin da ya zo musu da shi sihiri ne bayyananne, don haka ba za su bi shi ba.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman zunubin wanda ya ƙaga wa Allah ƙarya.

2. Duk da bayyanar hujjojin addinin Musulunci a fili maƙiya Musulunci ba za su daina ƙagar ƙarya suna danganta masa ba, domin ƙiyayyarsu ba ta rashin sanin gaskiya ce ba, ƙiyayya ce daga zuciya, domin buƙatarsu ita ce su disashe hasken Musulunci, amma ba za su yi nasara ba.

3. Duk fafutukar da maƙiya Musulunci suke yi ta hanyar kashe kuɗaɗe don su rushe addinin Musulunci ba za su taɓa yin nasara ba, domin busa ce kawai suke yi da bakunansu wai don su hure hasken Allah da ita, to ta yaya buƙatarsu za ta iya biya?

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin cika hasken addininsa a zamanin Annabi (ﷺ) da sahabbansa, ya kuma cika musu ni'imarsa, Musulmi da ma waɗanda ba Musulmi ba suka rayu ƙarƙashin inuwar amincinsa da adalcinsa. Hakanan kuma alƙawarin Allah zai tabbata a bayan ƙasa; Musulunci zai yaɗu ko'ina, Musulmi kuma za su sami kafuwa a bayan ƙasa yayin da suka koma kan karantarwar Littafin Allah da sunnar Manzonsa (ﷺ).

5. Abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi shi ne addinin gaskiya shi ne kuma shiriya, duk wanda ya nemi bauta wa Allah ba da abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi ba, to yana kan ɓata ne da kauce wa hanyar Allah.

6. Musulmi ba za su yi ƙarfi ba su samu kafuwa a bayan ƙasa har sai sun riƙe koyarwar Manzonsa (ﷺ) hannu bibbiyu, sun rungumi aiki na ƙwarai kai da fata, sannan ne nasarar Allah za ta zo musu, alƙawarin Allah ya tabbata a gare su.

Suratus Saff (7-9)

وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ وَهُوَ يُدْعَىٰٓ إِلَى ٱلْإِسْلَٰمِ ۚ وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ۝٧ يُرِيدُونَ لِيُطْفِـُٔوا۟ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفْوَٰهِهِمْ وَٱللَّهُ مُتِمُّ نُورِهِۦ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْكَٰفِرُونَ ۝٨ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُشْرِكُونَ ۝٩

7. Ba wanda kuma ya fi zalunci kamar wanda ya ƙaga wa Allah ƙarya, alhali kuwa shi ana kiran sa zuwa Musulunci. Allah kuma ba Ya shiryar da mutane azzalumai.

8. Suna nufin su dusashe hasken Allah da bakunansu, Allah kuwa Mai cika haskensa ne ko da kafirai sun ƙi.

9. Shi ne Wanda Ya aiko Manzonsa da shiriya da kuma addinin gaskiya don Ya ɗora shi a kan kowane addini, ko da kuwa mushirikai sun ƙi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana tabbatar da cewa, da'awar Musulunci da ƙarfafan hujjojinta sun zo wa mutane, to amma wasu da dama sun zaɓi su kafirce mata, su yaƙi manzannin Allah bisa zalunci, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babu wani azzalumi kamar wanda ya ƙirƙiri ƙarya ya jingina wa Allah, inda ya riƙa ɗaukar gumaka yana bauta musu ba Allah ba, alhalin shi kuma ana kiran sa zuwa Musulunci addinin kaɗaita Allah da bauta, an kuma bayyana masa hujjoji daban-daban amma saboda zaluncinsa ya sa ƙafa ya shure su; to ya sani Allah ba ya shiryar da mutane azzalumai, waɗanda suka cuci kansu da aikata shirka da saɓon Allah. Ba ma iya nan suka tsaya ba; suna ma ta ƙoƙarin ganin sai sun disashe hasken Allah da irin miyagun maganganunsu da suke yi don su ɓata Musulunci. To amma ko sun ƙi ko sun so, sai Allah ya cika addininsa, ya bayyana shi a ko'ina a bayan ƙasa, ya kuma ba shi rinjaye a kan sauran gurɓatattun addinai, ya ɗaukaka kalmarsa, domin kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne wanda ya aiko da Manzonsa Muhammadu ɗan Abdullahi (ﷺ) da addinin Musulunci, addinin shiriya mai ƙunshe da ɗimbin alherai, kuma addinin gaskiya mai ɗauke da ilimi mai matuƙar amfani da aiki nagari, domin ya ɗora shi a kan dukkan addinai ko da kuwa mushirikai suna ƙin haka. To tabbas sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kafa shi a bayan ƙasa da ƙarfin hujja da gamsassun bayanai.

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: "Dare da rana ba za su gushe ba har sai an bauta wa gumaka, watau Lata da Uzza." Ta ce na ce: Ya Manzon Allah, ni a da ina zaton cewa yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "*Shi ne wanda ya aiko da Manzonsa da shiriya da kuma addinin gaskiya don ya ɗora shi a kan dukkanin addinai ko da kuwa mushirikai sun ki*.", na zaci cewa hakan ya gama tabbata. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Nan gaba dai hakan zai kasance lokacin da Allah ya ga dama." [Muslim #2907].

An karɓo daga Saubanu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Allah ya tattaro mini duniya wuri guda sai na ga gabashinta da yammacinta, kuma lalle sai mulkin al'ummata ya kai inda aka tattaro mini daga gare ta." [Muslim #2889].

An karɓo daga Tamimuddari (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle wannan al'amari (wato Musulunci) sai ya kai duk inda dare da rana suka kai, Allah ba zai bar wani gidan laka ba ko na gashin raƙuma (wato birni da ƙauye) face sai ya shigar da wannan addinin cikinsa, da izzar mai izza ko

da ƙasƙancin ƙasƙantacce, izzar da Allah zai ɗaukaka Musulunci da ita da ƙasƙancin da zai ƙasaƙantar da kafirci da shi.” [Ahmad #16957].

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayan imani da Allah da Manzonsa (ﷺ), babu wani aikin da ya kai jihadi lada a wurin Allah.

2. Imani da Allah da jihadi don Allah suna daga cikin sababban shiga Aljanna.

3. Jihadi don Allah ya ƙunshi ciyar da dukiya don taimakon Musulunci da Musulmi da ba wa Musulunci kariya da rayuka da gangar jiki.

4. Imani da Allah da jihadi don Allah sababi ne na samun gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan iya gaggauto wa da mumini sakamakonsa tun a nan duniya kafin ya iske na lahira. Yakan kuma jinkirta masa shi har sai ya je lahira, Allah ba zai taɓa tozarta kyakkyawan aikin bawansa ba.

Suratus Saff (10-13)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ هَلۡ أَدُلُّكُمۡ عَلَىٰ تِجَٰرَةٖ تُنجِيكُم مِّنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ ۝١٠ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمۡوَٰلِكُمۡ وَأَنفُسِكُمۡۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ۝١١ يَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡ وَيُدۡخِلۡكُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ وَمَسَٰكِنَ طَيِّبَةٗ فِي جَنَّٰتِ عَدۡنٖۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ۝١٢ وَأُخۡرَىٰ تُحِبُّونَهَاۖ نَصۡرٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَفَتۡحٞ قَرِيبٞۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ۝١٣

10. Ya ku waɗanda suka yi imani, yanzu ba Na nuna muku ku wani ciniki da zai tserar da ku daga azaba mai raɗaɗi ba?

11. (Shi ne) ku yi imani da Allah da Manzonsa ku kuma yi jihadi don Allah da dukiyoyinku da rayukanku. Wannan shi ne ya fiye muku alheri, idan kun kasance kuna sane (da haka).

12. (Idan kun yi haka) zai gafarta muku zunubanku Ya kuma shigar da ku gidajen Aljanna (waɗanda) ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu da kuma wuraren zama masu kyau, a cikin gidajen Aljanna na dawwama. Wannan shi ne babban rabo.

13. Da kuma wata ɗayar da kuke so; (watau) nasara daga Allah da kuma buɗi a kusa. Ka kuma yi wa muminai albishir.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira muminai kira na musamman, domin ya kwaɗaitar da su a kan wani gagarumin aiki mai cike da tagomashi wanda ya kira shi da kasuwanci da zai tserar da su daga azaba mai raɗaɗi. Wannan kasuwanci mai riba kuwa shi ne, su yi imani da Allah da Manzonsa (ﷺ), su kuma yi jihadi don ɗaukaka addinin Allah ta hanyar aiki da dukiyoyinsu da kawunansu, su kuma daure ko da ransu ba haka yake so ba saboda wahalar da ke cikinsa. To amma su sani yin haka babban alheri ne a gare su in sun kasance sun san haka.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Hubshi Al-Khas’ami (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa, waɗanne ayyuka ne suka fi falala? Sai ya ce: “Imanin da babu kokwanto a cikinsa, da jihadin da babu satar ganima a cikinsa, da hajji karɓaɓɓiya.” [Nasa’i #4986].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa: Wane aiki ne ya fi falala? Sai ya ce: “Imani da Allah da Manzonsa.” Sai aka ce: Sai kuma me? Sai ya ce: “Jihadi domin Allah.” Sai aka ce: Sai kuma me? Sai ya ce: “Hajji karɓaɓɓiya.” [Bukhari #1519 da Muslim #83].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana gwaggwaɓar ribar da muminai za su samu idan sun shiga wannan kasuwanci, shi ne zai gafarta musu zunubansu manya da ƙanana, a ranar lahira kuma zai shigar da su gidajen Aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashin gine-ginensu da bishiyoyinsu, ya kuma shigar da su wasu wuraren zama masu kyau a cikin gidajen Aljanna na zama dindindin babu ranar fita daga cikinsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wannan sakamako nasu a lahira a matsayin babban rabo da babu wani rabo da ya kai shi daraja.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, bayan wancan rabo na lahira, akwai kuma wata ribar kuma ta duniya wadda zai gaggauto musu da ita wadda kuma suke matuƙar son ta, ita ce Allah ya ba su nasara a kan maƙiyansu, da kuma wani buɗi na kusa, watau cin garin Makka da yaƙi da ma wasu garuruwa bayansa da Allah zai faɗaɗa da’irar Musulunci da shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa ya yi wa muminai albishir da ganin abin da zai faranta musu rai na samun nasara a nan duniya da dacewa da babban rabo a lahira.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dole ne a cikin al’umma a samu waɗanda za su sadaukar da kansu don taimakon addinin Allah, ta hanyar yaɗa karatuttukansa da isar da shi ga mutane na birni da na ƙauye, da kuma haƙuri da juriya a kan haka. Wannan babbar falala ce ta kasancewa cikin rundunar Allah da Manzonsa.

2. Duk da kasancewar Manzo (ﷺ) ɗan aike ne daga Allah, kuma Allah ya ƙarfafe shi da mu’jizoji iri-iri masu nuna gaskiyarsa, to amma duk da haka yana buƙatar mataimaka wajen isar da saƙon Allah. Saboda haka, ashe dole ne kowane mai da’awa ya zamanto yana da masu taimaka masa wajen aikin isar da saƙon Allah da karantar da al’umma.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana taimakon muminai masu gaskiya yana ƙarfafar su ta hanyoyi daban-daban a kan abokan gabarsu har su yi nasara a kansu ta ɓangaren yaƙi ko ta ɓangaren ilimi da ƙarfin hujja.

4. Albishir ga muminai mabiya Annabi Muhammadu (ﷺ) da samun rinjaye a kan maƙiyansu, matuƙar sun tsaya a kan taimakon addinin Allah, domin idan har Allah ya ba wa Hawariyawa almajiran Annabi Isa nasara da rinjaye a kan maƙiyansu, to babu shakka al’ummar Annabi Muhammadu (ﷺ) ita ce ta fi cancantar samun irin wannan nasara domin girman darajar Annabin da Allah ya aiko musu da cikar addinin da ya ba su, da dacewarsa da kowane zamani da kuma kowace al’umma.

Suratus Saff (14)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُوٓاْ أَنصَارَ ٱللَّهِ كَمَا قَالَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ لِلۡحَوَارِيِّـۧنَ مَنۡ أَنصَارِيٓ إِلَى ٱللَّهِۖ قَالَ ٱلۡحَوَارِيُّونَ نَحۡنُ أَنصَارُ ٱللَّهِۖ فَـَٔامَنَت طَّآئِفَةٞ مِّنۢ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ وَكَفَرَت طَّآئِفَةٞۖ فَأَيَّدۡنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ عَلَىٰ عَدُوِّهِمۡ فَأَصۡبَحُواْ ظَٰهِرِينَ ١٤

14. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku zama masu taimaka wa (addinin) Allah, kamar yadda Isa ɗan Maryamu ya ce da Hawariyawa: “Su wane ne masu taimaka mini zuwa ga Allah?” Hawariyawan suka ce: “Mu ne masu taimaka wa Allah.” Sai wata ƙungiya daga Bani Isra’ila suka yi imani, wata ƙungiya kuma ta kafirta, sai Muka ƙarfafa waɗanda suka yi imani a kan maƙiyansu, sai suka wayi gari suna masu cin nasara.

A ayar ƙarshe ta wannan Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake jaddada kiransa ga muminai da su tashi tsaye su zama masu taimakon addinin Allah a koyaushe, su taimaka wa Manzon Allah (ﷺ) wajen yaɗa kiran Allah da isar da shi ko'ina a duniya, kamar yadda Hawariyawa almajiran Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suka taimaka masa wajen yaɗa addininsa, lokacin da ya tambaye su cewa, su wane ne za su taimaka masa zuwa ga Allah? Sai suka amsa masa da cewa, su ne waɗanda za su taimaki addinin Allah.

An karɓo daga Abdullah ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wani annabi gabanina da Allah ya aiko shi cikin al'ummarsa, sai ya kasance a cikin al'ummar tasa yana da hawariyawa da sahabbai waɗanda suke riƙo da sunnarsa, suke kuma koyi da umarninsa..." [Muslim#50].

Daga nan sai Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da yaɗa addinin Allah shi da Hawariyawa almajiransa, har ya zamanto an samu wata ƙungiya daga cikin Banu Isra'ila sun yi imani da shi, wasu kuma sun kafirce masa, sai Allah ya ƙarfafi waɗanda suka yi imani a kan maƙiyansu kafirai, sai suka wayi gari su ne masu rinjaye a kansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dukkan abubuwan da suke cikin sammai da na ƙasa suna yi wa Allah tasbihi, sannan kuma ya yi amfani da sigar aikin da ake cikin yi, watau '*suna yi masa tasbihi*', saɓanin yadda a surorin baya aka yi amfani da aikin da ya wuce, watau '*sun yi*', an kuma yi haka ne domin abin ya dace da babban jigon Surar, watau batun sallar Juma'a da tsawatar wa waɗanda suka watse suka bar Manzon Allah (ﷺ) a tsaye yana huɗuba a ranar Juma'a, don su tari ayarin fatake da suka zo Madina da kayan kasuwanci. Allah ya nuna wa muminai cewa, dukkan abubuwan da suke sammai da na ƙasa koyaushe cikin yi wa Allah bauta suke, babu abin da yake sanya su su bar wannan bautar, kamar yadda waɗannan muminai suka bar cikashe sallar Juma'a, domin harkar duniya. Sannan aka ambaci wasu kyawawan siffofi na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) don a jawo hankulansu su fahimci cewa mai irin waɗannan maɗaukakan siffofi ba ya dacewa ga mumini ya tafi ya bar halalarsa, ba tare da an kammala ibadar da ake yi ba, ko an sami izini daga gare shi.

2. Babbar ni'imar da Allah ya yi wa 'yan'adam gaba ɗaya, musamman kuma Larabawa, da ya aiko musu da Manzo wanda ya kuɓutar da su daga rayuwa irin ta jahiliyya marar kan gado.

3. Wata ni'ima kuma ta musamman ga Larabawa ita ce, kasancewar wannan Manzon daga cikin jinsinsu ya fito, ba a aiko musu wani baƙo ba, kamar yadda aka aika Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga mutanen Sadum, aka kuma aika Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga mutanen Ninawa da Annabi Ilyasu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da aka aika shi zuwa ga mutanen Saida, watau Kana'anawa masu bautar '*Ba'alu*'. Don haka kasancewar Manzo ya fito daga cikin jinsin Larabawa, wannan wata ni'ima ce ɗoriya a kan ni'imar shiryarwa da karantarwa da ya zo musu da ita.

4. Siffanta Annabi da cewa shi ma ummiyyi ne kamar Larabawan da aka aiko shi a cikinsu, shi ma wata ƙarin ɗaukaka ce da mu'ujiza a gare shi, domin duk da zamantowarsa ummiyyi sai ga shi ya zo da abin da ya zarce na sauran manzanni da aka aika su zuwa ga al'ummu masu wayewa da ci gaba na ilimi, kamar al'ummar Banu Isra'ila, watau Yahudawa da Nasara.

5. Albishir ga Annabi (ﷺ) da cewa da'awarsa za ta yaɗu har ta tsallake al'ummar Larabawa ta shiga cikin wasu al'ummun duniya waɗanda ma ba Larabawa ne ba, kamar al'ummun Farisawa da Armaniyawa da Kurdawa da Barbar da Rumawa da Turkawa da mutanen Sin da Indiyawa da mutanen ƙasashen Sudan da

sauransu. Wannan ɗaya ne daga mu’ujizar Alƙur’ani ta bayar da labaran gaibu waɗanda ba su auku ba lokacin da yake sauka sai bayan wasu lokuta masu tsawo suka auku.

62-Suratul Jumu’a

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan da wannan Sura ta shahara da shi a wurin sahabbai da littattafan tafsiri da na hadisi shi ne ‘*Suratul Juma’a*’. Ya zo cikin [*Sahihul Bukhari* #4897] daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “Mun kasance muna zaune a wurin Manzon Allah (ﷺ) sai aka saukar masa da *'Suratul Jumu’a*'....”
An kira ta da wannan suna ne saboda lafazin *‘Al-jumu’a’* da ya zo cikinta a aya ta 9, inda aka yi maganar fita sallar Juma’a.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya*, babu wani saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta
Ita ce Sura ta ɗari da shida (106) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta sauka bayan ‘*Suratut Tahrim*’ kafin ‘*Suratut Tagabun*’. Maganar Abu Huraira da ta gabata ta nuna ta sauka bayan yaƙin Khaibar wanda aka yi a shekara ta bakwai bayan hijira, domin a lokacin wannan yaƙi ne Abu Huraira ya musulunta.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha ɗaya ne (11).

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin babbar baiwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa wannan al’umma da ya aiko musu Manzonsa Annabi Muhammadu (ﷺ), ya tsamo su daga cikin ɓatan da suke ciki zuwa shiriya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗe su da yi masa biyayya da guje wa kwaikwayon Yahudawa ɓatattu.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Nuni zuwa ga girman Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ɗaukakarsa, domin haka ne dukkan halittu a ƙasa da sama suke yi masa tasbihi.
• Babbar baiwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Larabawa da sauran al’ummu na aiko musu da Manzonsa (ﷺ) don karantar da su addininsa, da ya yi musu kyakkyawar tarbiyya bayan a da sun kasance a cikin ɓata mai girma.
• Sukan Yahudawa waɗanda Allah ya ba su littafin Attaura amma suka ƙi yin aiki da shi, suka sassauya shi da son zuciyarsu tare da ƙaryata da’awarsu ta cewa su ne masoyar Allah.
• Umarni ga muminai da zuwa sallar Juma’a da zarar sun ji an kira salla a wannan ranar, da barin duk wata sabga, har sai an gama sallar Juma’a tare da yawaita ambaton Allah a ranar.
• Tsawatar wa muminai da suka fashe suka bar Manzon Allah (ﷺ) yana huɗubar Juma’a yayin da suka ji labarin isowar fatake da kayan abinci a Madina.

Suratul Jumu’a (1-4)

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ ٱلۡمَلِكِ ٱلۡقُدُّوسِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَكِيمِ ١ هُوَ ٱلَّذِي بَعَثَ فِي ٱلۡأُمِّيِّـۧنَ رَسُولٗا مِّنۡهُمۡ يَتۡلُواْ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمۡ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَإِن كَانُواْ مِن قَبۡلُ لَفِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٢ وَءَاخَرِينَ مِنۡهُمۡ لَمَّا يَلۡحَقُواْ بِهِمۡۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٣ ذَٰلِكَ فَضۡلُ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Duk abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa yana yin tasbihi ga Allah Sarki, Tsarkakakke, Mabuwayi, Mai hikima.

2. Shi ne wanda Ya aiko wa (Larabawa) ummiyyai (watau waɗanda ba sa karatu da rubutu) Manzo daga cikinsu, yana karanta musu ayoyinsa, yana kuma tsarkake su, kuma yana sanar da su Alƙur’ani da hikima, ko da yake a da can sun kasance cikin ƀata mabayyani.

3. Da kuma wasunsu (waɗanda) tukuna ba su riske su ba. Shi ne kuwa Mabuwayi, Mai hikima.

4. Wannan falala ce daga Allah, Yana bayar da ita ga wanda Ya ga dama. Allah kuwa Ma’abocin babbar falala ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da bayanin cewa, duk abin da yake sammai da wanda yake ƙasa suna yi masa tasbihi, watau suna tsarkake shi daga duk wani aibi da nakasa da duk abin da bai dace da shi ba. Shi ne cikakken Sarki wanda ya kaɗaita da mulkin duk abin da yake cikin sammai da wanda yake ƙasa. Tsarkakakke daga kowace irin tawaya. Mabuwayi wanda babu mai gagarar sa. Mai hikima a cikin halittarsa da shari’arsa da ƙaddararsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin babbar baiwa da ya yi wa wannan al’umma da ya aiko musu da Manzo daga cikin al’ummar Larabawa ummiyyai, watau waɗanda ba sa karatu ba sa rubutu, kamar yadda shi ma Manzon haka yake ba ya karatu da rubutu. Ya zo yana karanta musu ayoyin Littafin Allah da ya saukar masa, watau Alƙur’ani, yana kuma tsarkake su daga ƙazantar kafirci da ta shirka da ta miyagun ɗabi’u; yana kuma koyar da su hukunce-hukuncen Alƙur’ani da sunnarsa da bayanin ma’anonin ayoyin Allah. A da kafin zuwansa su Larabwa sun kasance suna rayuwa cikin duhu ne da ƀata mabayyani, domin ba su san komai ba sai bautar gumaka da aikata miyagun ɗabi’u na jahiliyya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, aiken Manzon Allah (ﷺ) bai taƙaita a cikin Larabawa kaɗai ba; ya haɗa har da wasu al’ummu daban waɗanda su ma saƙon zai kai gare su nan gaba, su yi imani da shi, su zamanto cikin al’ummarsa, domin shi Allah mabuwayi ne babu abin da ya fi ƙarfinsa, kuma mai hikima ne a halittarsa da shari’arsa da ƙaddararsa.

An karƀo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mun kasance muna zaune a wurin Manzon Allah (ﷺ) sai aka saukar masa ‘*Suratul Jumu’a’*, a cikinta Allah yake cewa: “*Da kuma wasu waɗanda tukunna ba su riske su ba*.”, Sai na ce: “Su wane ne waɗannan ya Manzon Allah?” Annabi bai amsa wa Abu Huraira tambayarsa ba, har sai da ya maimaita ta sau uku. Abu Huraira ya ce: Salmanu mutumin Farisa yana zaune cikinmu, sai Manzon Allah (ﷺ) ya dafa Salmanu da hannunsa ya ce: “Da a ce imani yana can wajen tauraron Surayya ne, to da wasu mazaje daga waɗannan sun kai gare shi.” [Bukhari #4897 da Muslim #2546].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan aike da ya yiwo na Manzonsa (ﷺ) wanda kuma ya shafi kowa da kowa, wata falalarsa ce da yake bayar da ita ga wanda ya ga dama, don haka ya zaƀi wannan al’umma ya yi mata wannan babbar baiwa, domin shi ma’abocin falala ne wadda take mai girma.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sukan duk mai ilimin da ba ya aiki da iliminsa.

2. Yahudawa sun zaɓi kafirci ne alhali suna sane, domin a cikinsu akwai waɗanda Allah ya ba wa ilimin Attaura amma suka take saninsu, suka ɓoye wa mabiyansu gaskiyar Manzon Allah da Alƙur'ani.

3. Duk malamin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi ilimi amma ya ƙi aiki da shi ko ya ɓoye wa mabiyansa gaskiya, alhalin ya san ta, to yana kama da malaman Yahudawa.

4. Karyata Yahudawa masu da'awar cewa, su ne zaɓaɓɓu a wurin Allah, kuma su kaɗai yake so ban da sauran mutane.

5. Dukkan wani masoyi yana begen haɗuwa da masoyinsa.

6. An hana Musulmi ya yi burin mutuwa, domin shi an umarce shi ne ya bauta wa Allah tsakanin tsoro da kyakkyawan fata, kuma rayuwarsa alheri ne a gare shi, domin zai ƙara yawaita kyawawan ayyukansa, sannan alheri ne ga wasu, domin za su amfana da shi. Yahudawa kuwa an neme su da su yi burin mutuwa, domin a ƙalubalanci da'awarsu ta ƙaryar cewa su kaɗai ne masoya Allah.

7. Tabbatar da mu'ujizar Alƙur'ani, domin ga shi ya tabbatar da cewa, Yahudawa ba za su iya burin mutuwa ba, kuma ba su iya yi ba.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rubuta mutuwa a kan kowa, don haka babu mai iya kuɓuce mata.

Suratul Jumu'a (5-8)

وَإِذۡ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوۡمِهِۦ يَٰقَوۡمِ لِمَ تُؤۡذُونَنِي وَقَد تَّعۡلَمُونَ أَنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُمۡۖ فَلَمَّا زَاغُوٓاْ أَزَاغَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُمۡۚ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡفَٰسِقِينَ ۝٥ وَإِذۡ قَالَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ إِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُم مُّصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيَّ مِنَ ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَمُبَشِّرَۢا بِرَسُولٖ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِي ٱسۡمُهُۥٓ أَحۡمَدُۖ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ قَالُواْ هَٰذَا سِحۡرٞ مُّبِينٞ ۝٦ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ وَهُوَ يُدۡعَىٰٓ إِلَى ٱلۡإِسۡلَٰمِۚ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ۝٧ يُرِيدُونَ لِيُطۡفِـُٔواْ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفۡوَٰهِهِمۡ وَٱللَّهُ مُتِمُّ نُورِهِۦ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡكَٰفِرُونَ ۝٨

5. Misalin waɗanda aka ɗora wa Attaura sannan ba su ɗauke ta ba, kamar misalin jaki ne da yake ɗauke da wagagen littattafai. Misalin mutanen da suka ƙaryata ayoyin Allah ya munana. Allah kuwa ba Ya shiryar da mutane azzalumai.

6. Ka ce: "Ya ku waɗanda suka zama Yahudawa, idan kun riya cewa ku ne masoyan Allah ban da sauran mutane, to ku yi burin mutuwa, idan kun kasance masu gaskiya ne."

7. Ba za su yi burin ta ba har abada saboda abin da hannayensu suka gabatar. Allah kuwa Masanin azzalumai ne.

8. Ka ce (da su): "Lalle ita mutuwar da kuke gudun ta, lalle za ta haɗu da ku; sannan za a mayar da ku wurin Masanin ɓoye da sarari, sannan Ya ba ku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake fito da bayanin girman ni'imar da ya yi wa wannan al'umma ta aiko musu Manzon Allah (ﷺ) a cikinsu, wanda a dalilinsu suka zarce duk sauran al'ummu da suka gabata, duk kuwa da kasancewar Larabawa ummiyyai ne lokacin da aka aiko shi, amma har sun zo sun fi Yahudawa falala da ɗaukaka, domin malamansu da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da su Attaura ya kuma umarce su da su yi aiki da ita su koyar da 'yan'uwansu hukunce-hukuncenta, domin su ma su yi aiki da ita, sun sa ƙafa sun take ilimin da Allah ya ba su, sun ƙi aiki da shi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, misalinsu kamar misalin jaki ne wanda yake ɗauke da wagagen littattafan ilimi a bayansa, amma bai san abin da yake ɗauke da shi ba, ballantana ya san darajarsa, kawai dai yana dakon wahala ne a bayansa, babu wata daraja da za su ƙara masa. To hakanan su ma waɗannan Yahudawan babu wata ɗaukaka da za su samu don sun san littafin Attaura amma ba su yi aiki da shi ba, ba su kuma amfana da abin da yake cikinsa na bushara da zuwan Manzon Allah (ﷺ) ba, don haka suka ci gaba da ƙaryata ayoyin da ya zo musu da su. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir da misalin waɗannan mutane azzalumai masu ƙaryata ayoyinsa, ya kuma tabbatar musu cewa, shi ba ya shiryar da azzaluman mutane waɗanda suka zaɓi kafirci suna sane.

Sannan kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani zaluncin na Yahudawa da cika bakinsu da taurin kansu, yayin da suke da'awar cewa, wai su ne masoyan Allah ban da sauran mutane, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da cewa ya kira su ya ƙalubalance su a kan wannan da'awar tasu cewa, su yi burin mutuwa idan har gaskiya suke faɗa na cewa, su ne masoyan Allah ban da sauran mutane, domin duk masoyi zai so gaggawar haɗuwa da masoyinsa, musamman idan yana da tabbacin cewa abin da zai samu a wurinsa ya fi wanda yake ciki.

To amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san ƙarya suke yi ba za su iya burin mutuwa ba har abada, sun ma fi burin su dawwama a duniya ko su yi tsawon rai saboda ayyukansu na kafirci da saɓon Allah da suka tabka a rayuwarsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) masani ne ga azzalumai, babu abin da zai ɓuya gare shi na ayyukansu, zai kuma yi musu sakayya a kai.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya tabbatar wa Yahudawa cewa, mutuwar nan da suke gudu babu makawa sai ta cim musu ko ba daɗe ko ba jima, domin Allah ya riga ya rubuta ta a kan kowanne ɗan'adam, don haka su ba bare ne ba. Idan kuma sun mutu to za a mayar da su ranar alƙiyama zuwa ga Allah Masanin abin da yake ɓoye da na sarari, sai ya ba su labarin duk abin da suka kasance suna aikatawa a duniya, ya kuma yi musu sakayya a kai.

Daga waɗannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sallar Juma'a wajibi ce a kan kowane mumini sai wanda aka ɗauke wa, kamar mata da yara da marar lafiya da matafiyi.

2. Muhimmancin halartar huɗubar Juma'a domin sauraron tunatarwa da wa'azi.

3. Umarni da yin kiran salla ranar Juma'a.

4. Haramta ciniki bayan kiran salla lokacin da liman ya hau mimbari.

5. Ya dace ga bawa yayin da yake tsaka da bautar Allah, idan ransa ya riya masa barin wurin ibadarsa don zuwa wani wargi ko neman duniya, to ya tunatar da zuciyarsa cewa, alherin da yake wurin Allah da samun yardarsa ya fi abin da ransa yake riya masa.

6. Huɗubar Juma'a ana gabatar da ita ne a tsaye ba a zaune ba.

Suratul Jumu’a (9-11)

هُوَ ٱلَّذِیٓ أَرۡسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلۡهُدَىٰ وَدِینِ ٱلۡحَقِّ لِیُظۡهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّینِ كُلِّهِۦ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡمُشۡرِكُونَ ۝٩ یَـٰۤأَیُّهَا ٱلَّذِینَ ءَامَنُوا۟ هَلۡ أَدُلُّكُمۡ عَلَىٰ تِجَـٰرَةٍ تُنجِیكُم مِّنۡ عَذَابٍ أَلِیمٍ ۝١٠ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتُجَـٰهِدُونَ فِی سَبِیلِ ٱللَّهِ بِأَمۡوَ ٰلِكُمۡ وَأَنفُسِكُمۡۚ ذَ ٰلِكُمۡ خَیۡرٌ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ۝١١

9. Ya ku waɗanda suka yi imani, idan aka yi kiran salla ranar Juma’a sai ku tafi zuwa zikirin Allah, kuma ku bar ciniki. Wannan (shi) ya fi muku alheri, idan kun kasance kuna sane (da haka).

10. Sannan idan aka gama salla sai ku bazu a bayan ƙasa ku kuma nema daga falalar Allah, kuma ku ambaci Allah da yawa don ku rabauta.

11. Idan kuma suka ga kasuwanci ko wasa sai su watse zuwa gare su, su bar ka a tsaye (kana huɗuba). Ka ce: “Abin da yake wurin Allah ya fi wasa da ciniki. Kuma Allah Fiyayyen masu arzutawa ne.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su yi gaggawa wajen halartar sallar Juma’a da zarar sun ji an yi kiran salla bayan liman ya hau mimbari, su kuma bar duk wata sabga ta saye da sayarwa, domin kada wannan ya ɗauke musu hankali har su rasa sallar Juma’a ko su je a makare. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, lalle wannan umarni da ya yi musu na halartar Juma’a da barin sabgogin kasuwanci shi ne ya fi musu alheri idan sun kasance sun san haka, don haka su yi iya ƙoƙarinsu wajen bin umarninsa da kiyaye haninsa.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, idan sun kammala sallar Juma’a, to sai su koma su ci gaba da harkokinsu na yau da kullum na neman halaliya, su kuma kiyaye wajen neman arzikinsu, su nemi aiki na halal da riba ta halal daga falalar Allah, amma kada su manta da ambaton Allah, su ambaci Allah sosai, domin su rabauta da samun abin da suke so, kuma su kuɓuta daga wanda suke ƙi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da labarin abin da ya faru ga wasu sahabbai lokacin da Manzon Allah (ﷺ) yake tsaye a kan mimbari ranar Juma’a yana huɗuba, sai suka sami labarin isowar ayarin fatake ɗauke da kayan kasuwanci, sai suka fashe suka bar Manzon Allah (ﷺ) tsaye tare da wasu mutane su goma sha biyu, suka nufi waɗancan fatake don sayen kayan masarufi a wurinsu.

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Muna tsaka da salla (yana nufin huɗuba) tare da Manzon Allah (ﷺ) sai wasu ayarin fatake suka shigo Madina ɗauke da abinci, sai mutane suka watse suka nufi wannan ayari, har ya zamanto mutum goma sha biyu ne kacal suka rage tare da Annabi (ﷺ), sai wannan ayar ta sauka. [Bukhari #936 da Muslim #863].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya soki wannan abu da ya faru, ya bayyana cewa, idan wasu daga Musulmi suka ga wani kasuwanci ko wasa, watau gangunan da attajiran suke bugawa idan sun iso gari domin sanar da mutane zuwansu, sai su watse su nufi inda wannan kasuwancin yake, su bar Manzon Allah (ﷺ) tsaye a kan mimbari yana huɗuba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya sanar da su cewa sakamakon kyakkyawan aiki da ke wurinsa ya fi wannan kasuwancin da wasan da suka bar sauraron huɗuba suka nufi wajensa, kuma haƙuri wajen biyar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya hana samun arzukin da Allah ya ƙaddara wa kowane bawa, domin shi ne fiyayyen mai arzutawa, don haka wanda ya ji tsoron sa ya kiyaye dokokinsa, to zai arzuta shi ta inda ba ya tsammani.

An karɓo daga Jabir ɗan Samura (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance yana yin huɗuba a tsaye.” [Muslim #862].

An karƀo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance yana yin huɗuba a ranar Juma'a a tsaye, sannan ya zauna, sannan kuma ya tashi ya sake yin huɗuba. [Bukhari #920 da Muslim #861].

An karƀo daga Jabir ɗan Samura (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) yana yin huɗubobi biyu (a ranar Juma'a), yana zama a tsakaninsu. Yana karanta Alƙur'ani ya kuma tunatar da mutane. [Muslim #862].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ware wannan Sura ɗungurungum don bayanin halayen munaukai, yana ƙara tabbatar da girman haɗarinsu da cutarwarsu ga Musulunci da Musulmi.

2. Imanin munafuki na ƙarya ne tun farko, don haka maganar fatar bakinsa ba za ta canza komai ba.

3. Karya babbar siffa ce a wurin munafukai.

4. Hatsarin yin rantsuwa a kan ƙarya, domin siffa ce irin ta munafukai marasa ganin girman Allah da darajar sunayensa masu tsarki.

5. Bayyana wa Musulmi saɓanin abin da yake cikin zuciya na wata gurɓatacciyar aƙida munafurci ne tsantsa ko da wasu sun kira shi da suna *'Taƙiyya'*, kamar a wurin mabiya addinin Shi'a.

6. Duk wanda munafurci ya yi masa katutu a zuciya, to babu wani alheri da zai shige ta har abada, sai idan Allah ne ya ga dama ya gyara shi.

7. Abin lura ga mutum shi ne, kyawon zuciyarsa ba kyan surarsa ko iya maganarsa ba.

8. Munafukai da ke gauraye da Musulmi su ne mafiya haɗari a cikin maƙiyansu, domin maƙiyi na fili ya fi sauƙin lamari a kan na ɓoye.

63-Suratul Munafiƙun

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan wannan Sura da ta Shahara da shi shi ne '*Suratul Munafiƙun*'. A wasu wurare an kira ta da '*Suratul Munafiƙin*'. [Dubi, Tirmizi #3600].
An kuma kira ta da wannan suna ne saboda ta yi bayanin wasu munafukan Madina a zamanin Manzon Allah (ﷺ).

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Babu wani saɓani a kan cewa Sura ce *Madaniyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ɗari da biyu (102) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta kuma sauka bayan '*Suratul Hajji'* kafin '*Suratul Mujadila'*. Kuma ta sauka ne bayan yaƙin *Banul Musɗaliƙ* wanda aka yi a shekara ta biyar bayan hijira.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha ɗaya ne (11) babu wani saɓani.

5. Sababin Saukarta:
An karɓo daga Zaidu ɗan Arƙam (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Mun fita a wata tafiya tare da Manzon Allah (ﷺ), sai mutane suka shiga wata matsananciyar wahala ta rashi, sai Abdullahi ɗan Ubayyu ya faɗa wa jama'arsa cewa: 'Kada ku ciyar da waɗanda suke wurin Manzon Allah (ﷺ) har sai sun waste daga wajensa.' Ya kuma ce: 'Lalle tabbas idan muka koma Madina lalle mai daraja zai fitar da wulaƙantacce daga cikinta.' Sai na garzayo na faɗa wa Manzon Allah wannan labari. Sai ya aika a kira masa Abdullahi ɗan Ubayyu ya kuma tambaye shi game da wannan labari da na zo masa da shi, sai ya yi iya rantsuwa cewa shi bai faɗi haka ba. Sai mutane suka riƙa cewa, Zaidu ya faɗa wa Manzon Allah (ﷺ) labarin ƙarya. Sai maganar mutane ta yi mini ciwo sosai a raina har sai da Allah ya saukar da tabbatar da gaskiyata game da faɗarsa: "*Idan munafukai suka zo maka*…." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya kirawo su don ya nema musu gafarar Allah sai suka kau da kawunansu suka bijire…." [Bukhari #4907 da Muslim #2772].

6. Babban Jigonta:
Tana tona asirin munafukai da bayanin siffofinsu da matsayin Musulunci da Musulmai a wajensu, don gargaɗi a kan koyi da su da kwaikwayon halayensu.

7. Daga Cikin Abubawan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tona yawancin halayen munafukai, kamar ƙarya da karya alƙawari da lalacewar aƙida da dagewa a kan ɓata da guje wa sauraron gaskiya da neman shiriya.
• Kwaɗaitar da muminai a kan ciyar da dukiyarsu domin Allah da yi wa ranar lahira kyakkyawan tanadi tun gabanin saukar ajali, watau mutuwa.

Suratul Munafiƙun (1-4)

إِذَا جَآءَكَ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ قَالُواْ نَشۡهَدُ إِنَّكَ لَرَسُولُ ٱللَّهِۘ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ إِنَّكَ لَرَسُولُهُۥۖ وَٱللَّهُ يَشۡهَدُ إِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ لَكَٰذِبُونَ ١ ٱتَّخَذُوٓاْ أَيۡمَٰنَهُمۡ جُنَّةٗ فَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ إِنَّهُمۡ سَآءَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٢ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ ءَامَنُواْ ثُمَّ كَفَرُواْ فَطُبِعَ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ فَهُمۡ لَا يَفۡقَهُونَ ٣ ۞وَإِذَا رَأَيۡتَهُمۡ تُعۡجِبُكَ أَجۡسَامُهُمۡۖ وَإِن يَقُولُواْ تَسۡمَعۡ لِقَوۡلِهِمۡۖ كَأَنَّهُمۡ خُشُبٞ مُّسَنَّدَةٞۖ يَحۡسَبُونَ كُلَّ صَيۡحَةٍ عَلَيۡهِمۡۚ هُمُ ٱلۡعَدُوُّ فَٱحۡذَرۡهُمۡۚ قَٰتَلَهُمُ ٱللَّهُۖ أَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Idan munafukai suka zo maka sai suka ce: “Muna shaidawa cewa lalle kai Manzon Allah ne.” Allah kuma Yana sane da cewa kai tabbas Manzonsa ne, kuma Allah Yana shaidawa cewa munafukai tabbas ƙarya suke yi.

2. Sun ɗauki rantse-rantsensu garkuwa, saboda haka suka kange (mutane) daga hanyar Allah. Lalle su abin da suka kasance suna aikatawa ya munana.

3. Wannan kuwa saboda cewa sun yi imani sannan suka kafirta, sai aka rufe zukatansu, saboda haka su ba sa fahimta.

4. Idan ka gan su sai jikkunansu su ƙayatar da kai; idan kuma suka yi magana za ka saurari maganarsu; kai ka ce su wasu gumaguman itatuwa ne a jingine; suna tsammanin kowace irin kururuwa saboda su ne. Su ne maƙiya, saboda haka ka yi hattara da su. Allah kuma Ya la’ance su; ta ina ne ake karkatar da su?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura ne da bayanin wata halayya ta yaudara da ƙarya ta munafukai yayin da suke zuwa wurin Manzon Allah (ﷺ) suna tabbatar masa tare da yin rantsuwa cewa, su lalle sun shaida cewa shi Manzon Allah ne wanda ya zo da saƙon gaskiya daga Allah, alhalin suna ɓoye kafirci a zukatansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa cewa yana sane da cewa shi Manzonsa ne na gaskiya, amma kuma ya tabbatar da cewa, munafukai maƙaryata ne kawai; ba da gaske suke shaidawa cewa shi Manzonsa ne ba, watau yaudara ce kawai irin tasu.
Kuma ya bayyana cewa, rantse-rantsen da suke yi a gaban Manzon Allah (ﷺ) duk na banza ne, domin sun mayar da su kamar wata garkuwa ce da suke kare kansu da ita daga kisa ko ɗauri, wannan kuma ya ba su damar hana mutane yin imani, saboda abin da suke ta yayatawa na ruɗani da maganganu masu tayar da fitina a bainar jama’a. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, abin da suke aikatawa na munafurci da rantse-rantsen ƙarya ya munana matuƙa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, babban abin da ya jawo musu faɗawa cikin wannan mummunan hali nasu shi ne, saboda sun yi imani ne tun farko irin na munafurci wanda bai kai har zuciya ba, sannan sai suka kafirce wa Allah a ɓoye, saboda haka sai Allah ya rufe musu zukatansu, imani ba ya shiga, ya zamanto ba sa fahimtar duk wata shiriya da ake nuna musu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin kyan surar ginin gangar jiki da kyan kama da ya yi musu ta yadda idan mutum ya gan su kamalar jikkunansu ta zahiri za ta ƙayatar da shi, a dalilin rayuwar jin daɗi da suke ciki, saboda haka da zarar sun buɗi baki suna magana sai ya kasa kunne ya yi ta sauraron su, don fasahar maganar da suke da ita. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mutum zai gan su a majalisin Manzon Allah (ﷺ) sundumdum a zaune kamar gumaguman itatuwa marasa amfani waɗanda aka jinige su, watau dai wannan cika fuskar duka fankanfayo ne ba sa fahimtar komai daga bayanan da Manzon Allah (ﷺ) yake yi, suna kuma ji a jikinsu duk wata kururuwa kansu za ta faɗa, saboda tsoro da rashin gaskiya. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi Manzonsa cewa, su fa maƙiyansa ne, ya yi hattara da

su kada su riƙa yaɗa sirrinsa ko su shirya masa wani makirci bai sani ba. Allah ya la’ane su, har ta yaya ake kawar da su daga yin imani tare da bayyanar dalilansa da ƙarfafan hujjojinsa a fili?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bijire wa sauraron nasiha da nuna girman kai, da ma siffa ce ta munafukai.

2. Duk wanda ya kafirta, to nema masa gafarar Allah ba zai amfane shi da komai ba a wurin Allah.

3. Duk wanda ya dage a kan bijire wa umarnin Allah da Manzonsa (ﷺ), to ba zai dace da samun shiriyar Allah ba.

Suratul Munafiƙun (5-6)
وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْا۟ يَسْتَغْفِرْ لَكُمْ رَسُولُ ٱللَّهِ لَوَّوْا۟ رُءُوسَهُمْ وَرَأَيْتَهُمْ يَصُدُّونَ وَهُم مُّسْتَكْبِرُونَ ۝٥ سَوَآءٌ عَلَيْهِمْ أَسْتَغْفَرْتَ لَهُمْ أَمْ لَمْ تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ لَن يَغْفِرَ ٱللَّهُ لَهُمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ۝٦

5. Idan kuma aka ce da su: “Ku zo Manzon Allah ya nema muku gafara,” sai su kau da kansu, sai ka gan su suna bijirewa, alhalin suna masu girman kai.

6. Duk ɗaya ne game da su, ka nema musu gafara, ko ba ka nema musu gafara ba, Allah ba zai gafarta musu ba har abada. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane fasiƙai.

A waɗannan ayoyi kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin tsananin taurin kan munafukai da mugun halinsu wanda yake ƙara tabbatar da munafurcinsu, shi ne duk sanda aka faɗa musu cewa, su je su samu Manzon Allah (ﷺ) su faɗa masa hanzarinsu game da mummunan abin da suka aikata, domin ya nema musu gafarar zunubbansu, sai su kawar da kawunansu domin yin izgili ga abin da suka ji, daga nan sai su bijire wa shawarar da aka ba su, suna nuna girman kai game da karɓar gaskiya da miƙa wuya gare ta. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana rashin amfanin nema musu gafara, ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, duk ɗaya ne ko ya nema musu gafara ko bai nema musu ba, domin shi Allah ba zai taba gafarta musu zunubansu ba, saboda sun tabbata cikakkun fasiƙai, Allah kuwa ba ya shiryar da fasiƙan mutane masu bijire wa ɗa’arsa da dagewa a kan saɓonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sanya wa Musulmi takunkumin tattalin arziki yana daga cikin hanyoyin da maƙiya Musulunci suke bi wajen yaƙar sa a kowane lokaci.

2. Abin mamaki ne ƙwarai zaton da munafukai suke yi na cewa sahabban Manzon Allah (ﷺ) sun tattara ne a gabansa domin neman abin da za su ci, don haka idan an hana su za su watse su bar shi. Wannan ya nuna irin yadda munafukai suka jahilci ainihin alaƙar sahabbai da Manzon Allah (ﷺ) waɗanda yawancinsu sun yiwo hijira ne daga garuruwansu sun bar dukiyoyinsu da sana’o’insu domin taimakon Musulunci, ba domin wani abin duniya ba.

3. Arziki duka na Allah ne, shi ne yake ba da shi ga wanda ya ga dama, ya hana wanda ya ga dama.

4. Ɗaukaka ta Allah ce gaba ɗayanta; shi ne yake ba da ita ga Manzonsa (ﷺ) da muminai. Kafiri kuwa duk irin matsayinsa a duniya ƙaskantacce ne a wurin Allah.

Suratul Munafiƙun (7-8)

هُمُ ٱلَّذِينَ يَقُولُونَ لَا تُنفِقُواْ عَلَىٰ مَنۡ عِندَ رَسُولِ ٱللَّهِ حَتَّىٰ يَنفَضُّواْۗ وَلِلَّهِ خَزَآئِنُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَلَٰكِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ لَا يَفۡقَهُونَ ٧ يَقُولُونَ لَئِن رَّجَعۡنَآ إِلَى ٱلۡمَدِينَةِ لَيُخۡرِجَنَّ ٱلۡأَعَزُّ مِنۡهَا ٱلۡأَذَلَّۚ وَلِلَّهِ ٱلۡعِزَّةُ وَلِرَسُولِهِۦ وَلِلۡمُؤۡمِنِينَ وَلَٰكِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ لَا يَعۡلَمُونَ ٨

7. Su ne waɗanda suke cewa: “Kada ku ciyar da waɗanda suke wurin Manzon Allah har sai sun dare”. Alhali kuwa taskokin sammai da ƙasa na Allah ne, sai dai kuma munafukai ba sa ganewa.

8. Suna cewa: “Tabbas idan muka koma Madina, lalle mafi daraja zai fitar da mafi wulaƙanci daga cikinta”. Alhali kuwa girma na Allah ne da Manzonsa da kuma muminai, sai dai kuma munafukai ba sa sanin (haka).

A waɗannan ayoyi kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fallasa wata mummunar magana da munafukai suke faɗa wa junansu ne game da Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa, yayin da suke ba wa junansu shawara a kan su daina kashe dukiyarsu suna ciyar da faƙirai da mutanen ƙauye da suke tare da Manzon Allah (ﷺ) har sai sun watse sun bar shi, watau su a tunaninsu, ba don wannan dukiyar da suke kashewa wajen ciyar da waɗannan sahabban ba, da ba za su iya zama da Manzon Allah (ﷺ) ba, kuma ba zai iya tattara su ba har su taimaki addinin Allah, don haka idan suka riƙe dukiyoyinsu suka hana su, to a ƙarshe duk za su watse su bar shi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, dukkan taskokin arziki da ke sammai da waɗanda suke a ƙasa nasa ne, yana arzuta wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, to amma su munafukai ba sa fahimtar haka, shi ya sa suke yin maganganunsu na jahilci da duhun kai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya fallasa wata mummunar magana da suka yi a kan Manzon Allah (ﷺ) yayin da shugabansu Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul ya buɗe baki ya furta har da rantsuwa cewa, lalle tabbas idan sun koma Madina daga wajen yaƙi, wai sai shi maɗaukaki tare da jama’arsa sun fitar da maƙaskanci, yana nufin Manzon Allah (ﷺ) da jama’arsa, daga birnin Madina.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da kyakkyawan martani a taƙaice da cewa, ai izza, watau ɗaukaka da daraja duka na Allah ne da Manzonsa da muminai, amma munafukai ba su san haka ba, don haka suke ganin su ne masu girma masu izza.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haɗarin dukiya da ‘ya’ya idan har suka shagaltar da bawa daga ambaton Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Kwaɗaitarwa a kan ciyar da dukiya don Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Wajibi ga mumini ya ribaci rayuwarsa ta duniya wajen shuka alheri saboda rayuwarsa ta lahira tun kafin lokacin mutuwarsa ya riske shi.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya wa kowane rai ajalinsa na mutuwa, idan ya riga ya zo, to ba za a saurara masa ko da daƙiƙa ɗaya ba.

Suratul Munafiƙun (9-11)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تُلۡهِكُمۡ أَمۡوَٰلُكُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُكُمۡ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٩ وَأَنفِقُواْ مِن مَّا رَزَقۡنَٰكُم مِّن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَ أَحَدَكُمُ ٱلۡمَوۡتُ فَيَقُولَ رَبِّ لَوۡلَآ أَخَّرۡتَنِيٓ إِلَىٰٓ أَجَلٖ قَرِيبٖ فَأَصَّدَّقَ وَأَكُن مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١٠ وَلَن يُؤَخِّرَ ٱللَّهُ نَفۡسًا إِذَا جَآءَ أَجَلُهَاۚ وَٱللَّهُ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١١

9. Ya ku waɗanda suka yi imani, kada dukiyoyinku da ‘ya’yanku su shagaltar da ku daga ambaton Allah. Duk wanda ya aikata haka kuwa, to waɗannan su ne taɓaɓbu.

10. Kuma ku ciyar daga abin da Muka arzuta ku tun kafin mutuwa ta zo wa ɗayanku sannan ya riƙa cewa: “Ya Ubangijina, me ya hana Ka saurara min zuwa wani ɗan lokaci na kusa sai in ba da gaskiya in kuma zama cikin bayi nagari.”

11. Allah kuwa ba zai taɓa saurara wa wani rai ba idan ajalinsa ya zo. Allah kuwa Masanin abin da kuke aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar wa muminai game da koyi da halaye na munafukai masu shagalta da rashin ambaton Allah, ya gargaɗe su cewa, kada dukiyoyinsu da ‘ya’yansu su ɗauke musu hankali game da ambaton Allah, watau salla da sauran farillan Musulunci da zikirin Ubangiji. Ya tabbatar musu cewa, duk wanda dukiyarsa da ‘ya’yansa suka shagaltar da shi game da abin da Allah ya wajabta masa, to waɗannan sun tabbata asararru a lahira waɗanda suka yi asarar kawaunansu da iyalansu. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su ciyar daga cikin dukiyoyin da ya arzuta su da su, tun kafin mutuwa ta zo wa ɗayansu a lokacin ya riƙa yin nadama a kan sakacin da ya yi, har ya riƙa roƙon Allah cewa, ina ma ya ɗan jinkirta masa zuwa wani ɗan lokaci kaɗan, don ya yi amfani da shi ya ba da sadaka daga dukiyarsa don Allah, ya zamanto cikin bayin Allah na ƙwarai waɗanda suka kyautata ayyukansu.
A nan ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai mayar masa da martani cewa, ba zai taɓa saurara wa wani rai ba idan ajalinsa ya zo, rayuwarsa ta duniya ta zo ƙarshe ke nan. Kuma Allah masanin abin da suke aikatawa ne, zai kuma saka wa kowa gwargwadon aikinsa mai kyau ko mummuna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Komai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halitta a sammai ko a ƙasa yana yi masa tasbihi wanda ya dace da irin halittarsa, duk da cewa mutane ba jin tasbihinsu suke ba. Wannan wani hannunka mai sanda ne ga mushirikai masu kafirce wa Ɗayantakar Allah da sanya masa abokan tarayya wajen bauta da ƙaryata ayoyinsa da Manzonsa (ﷺ) cewa, duk sauran halittu na sama da na ƙasa sun tabbatar da samuwar Allah mahaliccinsu, sun gaskata Ɗayantakarsa sun kuma bijire wa yi masa shirka ko kafirce masa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai daidaita mutane sun zama abu ɗaya a wurinsa ba; ya halicce su kashi biyu, wasu muminai masoyansa ‘yan Aljanna; wasu kuma kafirai maƙiyansa ‘yan wuta. Da’awar cewa duk mutane ɗaya suke ba su da wani bambanci, kafirce wa Alƙur’ani ce maganar mahaliccinsu.

3. Tunatar da mutane ni’imar kyawon halitta da ya yi musu, inda ya sanya halittar ɗan’adam ita ce mafi kyau cikin halittunsa, wanda ya wajaba su yi masa godiya a kan haka, ta hanyar yin imani da shi da manzanninsa da bautarsa shi kaɗai ba tare da yi masa shirka ba.

4. Wajibi ne a kan mumini ya gode wa Allah bisa zaɓar sa da ya yi ya sanya shi cikin rukunin muminai, ba rukunin kafirai ba, don haka ya wajaba ya ci gaba da yi wa Allah godiya a kan haka da yi masa biyayya cikin umarninsa da haninsa.

5. Kewayewar ilimin Allah ga komai, wata tsoratarwa ce ga ɗan'adam a kan ya guji saɓa wa Allah da bijire wa umarninsa da ɓoye wata mummunar aƙida a zuciyarsa, domin duk abin da yake tare da mutum mai kyau ko mummuna Allah yana sane da shi, kuma zai yi masa sakayya a kansa.

64-Suratut Taghabun

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta da '*Suratut Taghabun'* saboda a cikinta ne kawai wannan kalmar *At-Taghabun* ta zo a Alƙur'ani. Kalmar tana nufin kamunga ko asara.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya* a wurin mafi yawan malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ɗari da bakwai (107) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan '*Suratul Jumu'a'* kafin '*Suratus Saffi*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha takwas ne (18).

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin asara babba da kafirai za su tabka a ranar alƙiyama, don ya zama gargaɗi a gare su.

6. Daga Cikin Abubawan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Ɗaukacin halittun da suke cikin sammai da na ƙasa suna tsarkake Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Allah ne kaɗai mamallakin komai na haƙiƙa, don haka shi ya fi cancanta a kaɗaita da yabo da kirari.
• Bayan tabbatar cewa Allah ne ya halicci dukkan mutane, sai kuma daga cikinsu aka samu kafiri aka kuma sami mumini.
• Ni'imar Allah ga ɗan'adam da ya halicce shi da mafi kyau sura.
• Gargaɗi ga kafirai da su guji aiki irin na kafiran da suka gabace su waɗanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka, don kada su ma ya hallaka su bayan sun ƙaryata ayoyinsa bayyanannu sun yi girman kai.
• Sanar da su cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sane da komai na sarari da na ɓoye, har ma da abin da yake cikin zukatansu.
• Tsawatar wa kafirai masu ƙaryata zuwan ranar alƙiyama da tsoratar da su mummunan sakamako da yake jiran su idan ba su yi imani ba. Don haka idan suna son samun tsira a wannan rana, to su gaggauta yin imani da Allah da Manzonsa da littafinsa Alƙur'ani.
• Lallashin muminai game da cutarwar da mushirikai suke yi musu, da umartar su da su dogara ga Allah a cikin dukkan al'amuransu.
• Gargaɗin muminai game da biye wa son zukatan wasu 'ya'yansu da matansu, don su hana su yin hijira domin Allah.
• Umarni ga muminai da su ciyar da dukiyoyinsu don Allah da neman yardarsa.

Suratut Taghabun (1-4)

يُسَبِّحُ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۖ لَهُ ٱلۡمُلۡكُ وَلَهُ ٱلۡحَمۡدُۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ١ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ فَمِنكُمۡ كَافِرٞ وَمِنكُم مُّؤۡمِنٞۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ٢ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّ وَصَوَّرَكُمۡ فَأَحۡسَنَ صُوَرَكُمۡۖ وَإِلَيۡهِ ٱلۡمَصِيرُ ٣ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَيَعۡلَمُ مَا تُسِرُّونَ وَمَا تُعۡلِنُونَۚ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa yana tasbihi ga Allah; mulki nasa ne kuma yabo ya tabbata a gare Shi; kuma Shi Mai iko ne a kan komai.

2. Shi ne Wanda Ya halicce ku, don haka daga cikinku akwai kafiri, daga cikinku kuma akwai mumini. Allah kuwa Mai ganin abin da kuke aikatawa ne.

3. Ya halicci sammai da ƙasa da gaskiya, kuma Ya suranta ku, sannan Ya kyautata surorinku; zuwa gare Shi ne kuma makomarku take.

4. Yana sane da abin da yake cikin sammai da ƙasa, kuma Yana sane da abin da kuke ɓoyewa da abin da kuke bayyanawa. Allah kuma Masanin abubuwan da suke cikin zukata ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da bayanin cewa, abubuwan da suke sammai da na ƙasa suna tasbihi ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), watau suna tsarkake shi daga duk wata sifa ta nakasa ko aibu, saboda cikar ikonsa da mulkinsa, domin duk abin da yake cikin sammai da ƙasa mulkinsa ne shi kaɗai ba shi da abokin tarayya, kuma kyakkyawan yabo ya tabbata a gare shi, kuma mai iko ne a kan komai babu abin da yake gagarar sa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ɓangare na cikar ikonsa, domin shi ne ya halicci mutane baki ɗaya yadda ya ga dama ya samar da su, daga cikinsu akwai kafiri wanda makomarsa wutar Jahannama ce; akwai kuma mumini wanda makomarsa Aljanna ce, kuma shi mai ganin duk abubuwan da suke aikatawa ne kyawawan da munana, zai kuma yi musu sakayya a kai ranar alƙiyama.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da hikimar halittar sammai da ƙasa da cewa, ya halicce su ne da gaskiya, ba don wasa ba, ya kuma halicci mutane cikin mafi kyan surar halitta, ya suranta su cikin miƙaƙƙen diri, da ya ga dama da sai ya yi su munana, wannan kuwa wata falala ce a gare su, kuma gare shi ne kaɗai duk za a koma a ranar alƙiyama, don ya yi wa ƙowa sakayya a kan ayyukansa masu kyau ko munana.
Sai kuma Allah ya bayyana yalwar iliminsa da ya kewaye komai, yana sane da abin da yake cikin sammai da wanda yake a ƙasa, yana kuma sane da abin da mutane suke ɓoyewa na ayyuka da wanda suke bayyanawa, yana kuma sane da duk abin da ke cikin zukata na alheri ko na sharri, babu abin da zai ɓuya gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da wannan al'umma labaran al'ummun farko waɗanda ya hallakar saboda kafircinsu, domin wa'azi da nusarwa ga wannan al'umma ta guji aikata irin aikinsu, don guje wa mummunar makoma irin tasu. Wannan kuwa rahamarsa ce da luɗufinsa ga bayinsa.

2. Babbar hujjar da mushirikai suka maƙale wa don ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) ita ce kasancewarsa mutum irinsu, wai ta yaya zai zama shi ne Manzon Allah zuwa gare su? Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna

musu haɗarin abin da suke kai, domin da irin wannan hujja ce kafiran farko suka fake wajen ƙaryata manzanninsu, Allah kuma ya hallaka su gaba ɗayansu, don haka su ma mushirikai sai su shiga taitayinsu, don gudun faruwar irin haka a kansu.

3. Tabbatar da cewa, manzannin Allah mutane ne kamar sauran jinsin mutane, sai dai Allah ya zaɓe su ya yi musu wahayi.

4. Cikakkiyar wadatar Allah, don haka bautar masu bauta masa, ba za ta ƙare shi da komai ba, kafircin masu kafirce masa ma, ba zai cutar da shi da komai ba, kowa ya yi mai kyau don kansa, idan kuma ya munana ma don kansa.

Suratut Taghabun (5-6)
أَلَمْ يَأْتِكُمْ نَبَؤُاْ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَبْلُ فَذَاقُواْ وَبَالَ أَمْرِهِمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ۝٥ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُۥ كَانَت تَّأْتِيهِمْ رُسُلُهُم بِٱلْبَيِّنَٰتِ فَقَالُوٓاْ أَبَشَرٌ يَهْدُونَنَا فَكَفَرُواْ وَتَوَلَّواْ ۚ وَّٱسْتَغْنَى ٱللَّهُ ۚ وَٱللَّهُ غَنِيٌّ حَمِيدٌ ۝٦

5. Yanzu labarin waɗanda suka kafirta gabaninku bai zo muku ba? Ai sun ɗanɗani uƙubar kafircinsu (a duniya), suna kuma da azaba mai raɗaɗi (a lahira).

6. Wannan kuwa saboda lalle manzanninsu sun kasance suna zuwa musu da ayoyi bayyanannu, sai suka ce: “Yanzu mutane ne za su shiryar da mu?” Saboda haka suka kafirce suka kuma ba da baya, Allah kuma Ya wadatu. Allah kuma Mawadaci ne Sha-Yabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi mushirikai masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da tashin alƙiyama, inda ya ja hankalinsu da cewa, shin ba su sami labarin kafiran da suka gabace su ba, kamar al’ummar Annabi Nuhu da Samudawa da Adawa da mutanen Fir’auna, waɗanda suka kafirce wa manzanninsu, don haka suka ɗanɗani kuɗar azabar Allah mai raɗaɗi? Babu shakka sun samu waɗannan labaran, sun san su sarai, don haka ta zama wajibi su ɗauki izina daga gare su, su zamo musu wa’azantuwa, su tuba zuwa ga Allah don gudun su ma azabar Allah mai tsanani ta sauka a kansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan aikin da kafiran farko suka yi har ya hallaka su da cewa, saboda manzanninsu sun kasance suna zuwa musu daga wajensa da ƙarfafan hujjoji bayyanannu, to amma sai suka sa ƙafa suka shure su da hujjar cewa, wai ta ƙaƙa zai yiwu a aiko musu da manzanni daga jinsinsu mutane a ce kuma su ne za su nuna musu gaskiya? Sai suka kafirce suka kuma bijire wa yin imani da su. To wannan kuma ba wani abu ne da zai cutar da Allah da komai ba, domin shi ya wadatu da su, ba ya buƙatar imaninsu ko ɗa’arsu, domin ɗa’arsu ba za ta ƙare shi da komai ba a cikin mulkinsa, Allah mai cikakkiyar wadata ne ba ya neman komai a wurin bayinsa, kuma shi sha-yabo ne a kan maganganunsa da ayyukansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk masu ƙaryata ranar alƙiyama suna ƙaryatawa ne ba da wata hujja ba sai kawai riyawa da fatar baki, domin dukkan dalili na zahiri suna nuna tabbatar aukuwar ranar sakamako ga dukkan halittun da Allah ya yi.

2. Halaccin yin rantsuwa da Allah, don tabbatar da wata gaskiya da wani yake musunta ta, ba tare da wata ƙwaƙƙwarar hujja ba, domin kawar masa da duk wani kokwanto daga zuciyarsa.

3. Daga cikin hanyoyin da za su taimaka wa bawa a kan aiki nagari, akwai tunawa da ranar da mutane masu ɗimbin yawa za su tabka babbar asara, watau ranar alƙiyama.

4. Imani da Allah da kyakkyawan aiki, shi ne yake zama sanadiyyar samun shiga gidan Aljanna. Kamar yadda kafirce wa Allah da ƙaryata ayoyinsa, yake zama sanadiyyar shiga wutar Jahannama.

Suratut Taghabun (7-10)

زَعَمَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَن لَّن يُبۡعَثُواْۚ قُلۡ بَلَىٰ وَرَبِّي لَتُبۡعَثُنَّ ثُمَّ لَتُنَبَّؤُنَّ بِمَا عَمِلۡتُمۡۚ وَذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٧ فَـَٔامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلنُّورِ ٱلَّذِيٓ
أَنزَلۡنَاۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ٨ يَوۡمَ يَجۡمَعُكُمۡ لِيَوۡمِ ٱلۡجَمۡعِۖ ذَٰلِكَ يَوۡمُ ٱلتَّغَابُنِۗ وَمَن يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ وَيَعۡمَلۡ صَٰلِحٗا يُكَفِّرۡ عَنۡهُ سَيِّـَٔاتِهِۦ وَيُدۡخِلۡهُ
جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٩ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلنَّارِ خَٰلِدِينَ
فِيهَاۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ١٠

7. Waɗanda suka kafirta sun riya cewa ba za a tashe su ba har abada. Ka ce: “A’a, na rantse da Ubangijina tabbas za a tashe ku, sannan kuma tabbas za a ba ku labarin abin da kuka aikata. Wannan kuwa mai sauƙi ne a wurin Allah.

8. “To ku yi imani da Allah da Manzonsa da kuma hasken da Muka saukar (watau Alƙur’ani). Allah kuma Masanin abin da kuke aikatawa ne.

9. “A ranar da zai tara ku a ranar taruwa; wannan kuwa ita ce ranar kamunga. Duk kuwa wanda ya yi imani da Allah ya kuma yi aiki nagari zai kankare masa zunubansa, Ya kuma shigar da shi gidajen Aljanna (waɗanda) ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu har abada. Wannan shi ne babban rabo.”

10. Waɗanda kuwa suka kafirce suka kuma ƙaryata ayoyinmu, waɗannan su ne ‘yan wuta, suna masu dawwama a cikinta; makoma kuwa ta munana.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda mushirikai suke ƙaryata tashi bayan mutuwa da zuwan ranar lahira, har suna dagewa suna riya cewa, ai ba fa za a tashe su bayan mutuwarsu ba, ba kuma tare da nuna wani dalili ko hujja ba in ban da magana ta molon-ka kawai. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya mayar musu da martani cewa, haka maganar take, ya rantse musu da Ubangijinsa a kan cewa, lalle za a sake tashin su a ranar alƙiyama, sannan kuma za a ba su labarin duk abin da suka aikata a duniya, kuma ya tabbatar musu cewa, sake tashinsu da rai bayan mutuwarsu abu ne mai matuƙar sauƙi a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), domin shi ne ya halicce su tun karon farko, don haka shi mai cikakken iko ne da zai sake tashin su da rai, don yi musu hisabi da sakamako a kan ayyukansu. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci ɗaukacin mutane a kan su yi imani da shi da Manzonsa da Alƙur’ani wanda yake haske ne da ya saukar wa Manzonsa, kuma shi masanin duk abin da suke aikatawa ne, babu abin da zai ɓuya gare shi daga cikin ayyukansu, kuma zai yi musu sakayya a kansu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya tuna musu ranar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai tara su, watau ranar babban taro na alƙiyama, don ya yi wa kowa sakayya a kan abin da ya aikata, wannan ranar a wurin kafirai ita ce ranar kamunga, watau ranar da za su ga asara ta bayyana a gare su a fili, inda muminai za su gaje gidajen kafirai a Aljanna, su kuma kafirai su gaje gidajen ‘yan Aljanna a wuta, don haka babu asara mai muni da ta kai wannan.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda wannan babbar riba da muminai za su samu da kuma mummunar asarar da za ta samu kafirai, inda ya bayyana cewa, duk wanda ya yi imani da Allah ya kuma yi kyakkyawan aiki nagari, to Allah zai kankare masa zunubansa, ya kuma shigar da shi gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su kuma zauna a cikinsu har abada babu mai fitar da su, kuma ni'imominsu ba za su yanke ba, don haka wannan sakamako da Allah ya yi musu, shi ne babban rabo da babu kamarsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kuma bayyana cewa, su kuma waɗanda suka kafirce masa, suka kuma ƙaryata ayoyinsa da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ), to waɗannan su ne 'yan wuta, kuma masu dawwama a cikinta har abada, wannan makoma tasu kuwa ta yi muni ƙwarai da gaske.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne a kan kowane mumini ya yi imani da Kaddarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), watau ya yi imani da cewa, duk wani abu da yake faruwa a ko'ina Allah yana sane da shi, kuma ya riga ya rubuta shi, kuma shi ne mahaliccinsa, yana kuma faruwa ne da izininsa da kuma ganin damarsa.

2. Amfanin yin imani da Kaddara shi ne, bawa zai samu nutsuwar zuciya da kwanciyar hankali da gwaggwaɓan sakamako mai kyau daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Aikin manzannin Allah shi ne isar da saƙonsa, amma jefa shiriya a cikin zukata, wannan aikin Allah ne shi kaɗai.

4. Wajibi ga bawa mumini ya dogara ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a cikin dukkan al'amuransa.

Suratut Taghabun (11-13)
مَآ أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَمَن يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ يَهۡدِ قَلۡبَهُۥۚ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١١ وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَۚ فَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَإِنَّمَا
عَلَىٰ رَسُولِنَا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ١٢ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ١٣

11. Ba wata musiba da ta samu sai da izinin Allah. Duk kuwa wanda ya yi imani da Allah zai shiryi zuciyarsa. Allah kuma Masanin komai ne.

12. Ku bi Allah kuma ku bi Manzon. To idan kuka ba da baya to abin da yake kan Manzonmu kawai shi ne isar da aike.

13. Allah, babu wani abin bauta da gaskiya sai Shi, to sai muminai su dogara ga Allah kawai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin muminai a kan su yi imani da Kaddara mai daɗi da mara daɗi, ya kuma bayyana musu babban tagomashinsa a kan hakan, da cewa, babu wata musiba da za ta samu wani a karan kansa ko a dukiyarsa ko a 'ya'yansa sai da izinin Allah, watau hukuncinsa da ƙaddararsa, don haka sai ya sallama wa Allah lamarinsa baki ɗaya, domin kuwa duk wanda ya yi imani da Allah da hukuncinsa da ƙaddararsa, to zai shiryar masa da zuciyarsa ya sanya ta miƙa wuya ga hukuncinsa da yarda da ƙaddararsa, Allah masanin komai ne, babu abin da yake ɓuya a gare shi.

An karɓo daga Suhaibu (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Akwai abin al'ajabi ga al'amarin mumini, domin dukkan al'amarinsa alheri ne a gare shi, hakan kuwa ba ya samuwa ga wani sai

dai mumini; idan abin farin cikin ya same shi sai ya yi godiya, sai ya zame masa alheri; idan kuwa wata cuta ce ta same shi sai ya yi haƙuri, sai ya zame masa alheri." [Muslim #2999].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci muminai da su yi masa ɗa'a, su kuma yi wa Manzonsa (ﷺ) ɗa'a, idan kuwa har suka bijire wa umarnin Manzonsa da yi masa ɗa'a, to su sani laifin bijirewarsu yana kansu su kaɗai, shi dai Manzo isar da saƙon Allah ne kaɗai nasa, kuma ya riga ya isar babu sauran bashi a kansa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da Kaɗaitakarsa da cewa shi ne Allah wanda babu wani abin bauta da gaskiya sai shi kaɗai, don haka yake umartar muminai da su dogara da shi shi kaɗai cikin dukkan al'amuransu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gargaɗi ga muminai a kan kada su yi sakaci har son matansu ko 'ya'yansu ya kai su ga saɓon Allah ko barin abin da ya wajabta musu. An umarci mutum da ya yi hattara da su ne saboda kasancewarsu tare da shi a koyaushe, sannan kuma a ɗabi'ance Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya dasa soyayyarsu a cikin zukata.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya yi umarni da yi wa mata da 'ya'ya rangwame da afuwa don kada a ɗauki gargaɗi a kansu a matsayin umarni ne na a gallaza mu'amala da su, musamman yayin da za su yi wani laifi. Sai Allah ya kwaɗaitar a kan yi musu afuwa da rangwame da gafara.

3. Duk wani abu da aka wajabta wa bawa aikata shi, to yakan faɗi daga kansa idan ya zamanto ba shi da ikon aikata shi. Idan mutum zai iya aikata wani ɓangare na abin da aka wajabta masa, amma ba zai iya yin sa gaba ɗaya ba, to zai aikata abin da zai iya ne kawai sauran kuma ya faɗi daga kansa, kamar yadda Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Idan na yi muku wani umarni, to ku yi abin da za ku iya daga cikinsa." [Bukhari #7277 da Muslim #1337].

4. Kwaɗaitarwa a kan ciyar da dukiya don Allah da gwaggwaɓan ladan da Allah ya tanadar wa mai aikata haka, da kuma gargaɗi game da rowa da asarar da marowaci yake gamuwa da ita.

Suratut Taghabun (14-18)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّ مِنۡ أَزۡوَٰجِكُمۡ وَأَوۡلَٰدِكُمۡ عَدُوّٗا لَّكُمۡ فَٱحۡذَرُوهُمۡۚ وَإِن تَعۡفُواْ وَتَصۡفَحُواْ وَتَغۡفِرُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ١٤ إِنَّمَآ أَمۡوَٰلُكُمۡ وَأَوۡلَٰدُكُمۡ فِتۡنَةٞۚ وَٱللَّهُ عِندَهُۥٓ أَجۡرٌ عَظِيمٞ ١٥ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ مَا ٱسۡتَطَعۡتُمۡ وَٱسۡمَعُواْ وَأَطِيعُواْ وَأَنفِقُواْ خَيۡرٗا لِّأَنفُسِكُمۡۗ وَمَن يُوقَ شُحَّ نَفۡسِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ١٦ إِن تُقۡرِضُواْ ٱللَّهَ قَرۡضًا حَسَنٗا يُضَٰعِفۡهُ لَكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ شَكُورٌ حَلِيمٌ ١٧ عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١٨

14. Ya ku waɗanda suka yi imani, lalle wasu daga matanku da 'ya'yanku maƙiyanku ne, sai ku yi hattara da su. Idan kuma kuka yafe kuka kau da kai, to lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

15. Dukiyoyinku da 'ya'yanku fitina ne kawai (a gare ku). Kuma a wurin Allah lada mai girma yake

16. Saboda haka ku kiyaye dokokin Allah gwargwadon ikonku, kuma ku yi sauraro, ku bi, ku kuma ciyar, shi ya fi alheri a gare ku. Duk kuwa wanda aka kare shi daga tsananin son kansa, to waɗannan su ne masu babban rabo.

17. Idan kuka ranta wa Allah kyakkyawan rance, to zai ninninka muku shi, Ya kuma gafarta muku. Allah kuma Mai godewa ne, Mai haƙuri..

18. Masanin ɓoye da sarari ne, Mabuwayi, Mai hikima.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira muminai ya ja hankalinsu a kan su yi hattara da matansu da 'ya'yansu, kada su biye musu a kan komai har su kai su su baro, ya tabbatar musu cewa, a cikin matansu da 'ya'yansu akwai maƙiyansu waɗanda suke ƙoƙarin hana su ɗa'ar Allah ko su jefa su cikin saɓon Allah, kamar waɗanda za su hana su ambaton Allah ko fita jihadi don ɗaukaka addininsa, su riƙa sage musu gwiwa suna daƙile su a kan duk wani aikin alheri da suka ɗauko. Allah ya umarce su da cewa, lalle su yi hattara da irin waɗannan mata da 'ya'ya, kada su kuskura su bar su har su yi musu sakiyar da ba ruwa.
Amma kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, ba yana umartar su ba ne a kan su guji matansu da 'ya'yansu baki ɗaya, ko su riƙa gallaza musu ta hanyar yi azabtar da su. Duk da haka yana umartar su da yi musu afuwa idan sun yi laifi, su kawar da kai su rufa musu asiri su yafe musu, domin su ma suna son Allah ya gafarta musu nasu laifukan, don haka idan suka yi wa wasu gafara, su ma sai Allah ya gafarta musu, domin shi mai gafara ne mai jin ƙai.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wannan ayar ta sauka ne game da wasu mutanen Makka waɗanda suka musulunta, suka yi niyyar yin hijira zuwa ga Annabi (ﷺ), to amma sai matansu da 'ya'yansu suka ki yarda su ƙyale su su yi hijira. To lokacin da suka sami damar yin hijira suka zo Madina sai suka sami mutane tuni sun yi nisa wajen fahimtar addini, wannan ya sa suka yi niyyar sai sun yi wa matansu da 'ya'yansu uƙuba, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan ayar." [Tirmizi #3605].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, dukiyoyi da 'ya'ya da yake bai wa mutane wata jarraba ce a gare su, domin za su iya sanya su neman dukiya ta haramun da barin ɗa'a ga Allah, amma lada mai girma yana wurin Allah ga duk wanda ya fifita yi masa biyayya a kan biye wa son 'ya'yansa ko shagaltuwa da tara dukiya da manta biyar sa. Babban sakamakon da Allah ya tanadar wa mai yi masa ɗa'a kuwa shi ne gidan Aljanna.

An karɓo daga Buraida ɗan Husaib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Annabi (ﷺ) yana tsakar yin huɗuba sai ga Hasan da Husaini sun tafo sanye da jajayen riguna, suna tafiya suna tuntuɓe suna faɗuwa, sai Manzon Allah (ﷺ) ya sauko daga kan mimbari ya ɗauke su a hannayensa, sannan ya ce: "Allah ya yi gaskiya inda ya ce: 'Dukiyoyinku da 'ya'yanku fitina ne kawai a gare ku.' Lalle lokacin da na ga waɗannan yara ƙanana guda biyu suna tafiya suna tuntuɓe, sai na kasa haƙuri, har sai da na dakatar da maganata, na sauka inda suke." [Ahmad #22995 da Abu Dawud #1109 da Tirmizi #3774].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce su da su kiyaye dokokinsa, su bi umarninsa, su guje wa haninsa gwargwadon ikonsu, su kuma saurari wa'azin da Allah da Manzonsa (ﷺ) suke yi musu, su bi umarninsu da aiki da hukunce-hukuncen da aka shar'anta musu, su kuma ciyar da dukiyarsu wadda Allah ya arzuta su da ita, ta hanyoyin alheri da kyautatawa, su guji rowa da tsananin mammaƙo da dukiyarsu, duk wanda aka tsare shi daga tsananin son kansa da rowa, to masu irin wannan ɗabi'a su ne masu rabauta da samun abin da suke nema da kuɓuta daga abin da suke ƙi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar da su a kan ba da dukiyarsu don Allah, ya yi musu alƙawarin cewa, idan har sun ba shi kyakkyawan rance ta hanyar ciyar da dukiyarsu dominsa, to zai ninninka musu ladansu, watau duk wani kyakkyawan aiki ɗaya zai ninka musu shi gida goma, har zuwa ninki ɗari bakwai, har zuwa ninkin ba ninkin mai yawa, kuma sannan zai gafarta musu zunubansu domin shi mai

godiya ne, a kan ɗan ƙanƙanin aiki sai ya bayar da sakamako mai yawa, kuma mai haƙuri ne ba ya gaggauto da uƙubarsa ga wanda ya saɓa masa, yakan saurara masa don ya tuba sai ya yafe masa.
Sai kuma a ƙarshen Surar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da faffaɗan iliminsa wanda ya kewaye komai, na ɓoye da na sarari, babu abin da zai iya ɓuya a gare shi, mabuwayi ne wanda babu mai gagarar sa, mai hikima ne cikin halittarsa da ayyukansa da shari'arsa da ƙaddararsa.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sunnar sakin mace a shari'ance shi ne, mijinta ya sake ta bayan ta yi tsarkin haila ba tare da ya kusance ta ba a wannan tsarkin, ko kuma ya sake ta bayan cikinta ya bayyana, kuma ya zamanto saki ɗaya ne, ba biyu ko uku a dunƙule ba. Wannan shi ne sakin sunna da shari'a ta amince da shi. Duk sakin da ya saɓa wa wannan shi ake ce wa sakin bidi'a, watau kamar ya sake ta tana cikin al'ada ko bayan ya kusance ta, ko ya yi mata fiye da saki ɗaya a lokaci ɗaya ko a majlisi guda. Wannan duka haramun ne bai halatta ba.

2. Hikimar haramta yin saki a lokacin al'adar mace shi ne, don kada a cutar da ita ta hanyar tsawaita mata iddarta, domin ko da ta yi tsarki bayan wannan al'adar da aka yi mata saki a cikinta, ba za ta lissafa iddarta da wannan al'adar ko tsarkin ba, sai dai ta jira tsarki uku na gaba masu zuwa; ka ga an tsawaita mata kwanakin iddarta.
Hakanan idan miji ya saki matarsa da ciki wanda ba a sani ba, to zai iya zama matsala game da tantance uban ɗa bayan ta yi aure, ko kuma sha'anin gado.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni da kula da ƙidayar kwanakin idda wadda mace za ta yi da jinin haila, ko wadda za ta yi da watanni idan ba ta jinin haila, ko kuma mace mai ciki, domin game da lura da wannan ƙidayar akwai tsare haƙƙin Allah da haƙƙin mijin da ya yi sakin da haƙƙin wanda zai aure ta daga baya da kuma haƙƙin ciyarwarta da matsuguninta. To idan aka kiyaye lissafin iddarta za ta san komai nata kai-tsaye da haƙƙoƙinta da haƙƙoƙin da suke kanta. Wannan umarni na kula da ƙidayar idda ya shafi mijin da matar ko waliyyinta idan ba baliga ba ce.

4. Ba ya halatta ga mijin da ya saki matarsa saki na ɗaya ko na biyu ya kore ta daga gidansa. Dole ne ya bar ta har sai ta ƙare iddarta, domin a tsawon lokacin da za ta ɗauka tana idda tana matsayin matarsa ne, igiyar aurensu ba ta gama tsinkewa ba, don haka dole ne ya ba ta matsuguni da ci da sha har ta ƙare zaman iddarta. Ita ma haramun ne a gare ta ta fice ta bar masa gidansa da zarar ya sake ta saki na ɗaya ko na biyu, domin yin haka shiga haƙƙin mijinta ne.

5. Ya halatta miji ya fitar da matar da ya saka daga gidansa idan an same ta da laifi bayyananne wanda ba zai yiwu a ƙyale ta ta ci gaba da zama a gidan ba, kamar laifin zina ko sata ko cin mutuncin mutanen gidan, watau dangin mijinta, ko neman tashin hankali da su. Kamar yadda ita ma tana iya ficewa idan an samu wata lalura, kamar rashin tsaro a gidan ko rushewar gidan, ko ambaliyar ruwa, ko gobara da makamantansu.

65-Suratuɗ Ɗalaƙ

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan da ta shahara da shi a littattafan tafsiri da hadisi da masahifu shi ne '*Suratuɗ Ɗalaƙ'*. Amma an samu cewa Abdullahi ɗan Mas'ud ya kira ta da '*Suratun Nisa'il Kusra'*, watau Surar Nisa'i gajeriya, yana nufin ba doguwa da aka fi sani ba. [Dubi, Bukhari #4532].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya*babu wani saɓani a tsakanin malamai a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tis'in da shida (96) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Insan'*kafin '*Suratul Bayyina'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha biyu ne (12) a wurin yawancin malamai, amma a wurin mutanen Basra goma sha ɗaya ne (11).

5. Babban Jigonta:
Bayanin hukunce-hukuncen saki da abin da yake biyo bayansa na idda da shayarwa, da bayanin kyakkyawar aƙibar taƙawa da kuma mummunar aƙibar ƙetare iyakokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Daga Cikin Abubawan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Hukunce-hukuncen saki da idda da shayarwa da ciyarwa da tsugunarwa.
• Hikimar shar'anta yin idda.
• Hani game da cutar da matan da aka sake su aka ƙuntata musu.
• Kafa shaidu a kan saki da kome.
• Shawara tsakanin iyaye game da sha'anin 'ya'yansu.
• Bayanin muhimmancin kiyaye dokokin Allah, watau *taƙawa*da dogaro ga Allah.
• Wa'azi da tsoratarwa a kan saɓa wa dokokin Allah da ɗaukar izina daga al'ummun da suka saɓa wa manzanninsu, a ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su.
• Bayanin girman sha'anin wahayi, domin shi magana ce saukakkiya daga Allah masani kuma mai iko a kan komai.

Suratuɗ Ɗalaƙ (1)
يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِىُّ إِذَا طَلَّقْتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَطَلِّقُوهُنَّ لِعِدَّتِهِنَّ وَأَحْصُوا۟ ٱلْعِدَّةَ ۖ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ رَبَّكُمْ ۖ لَا تُخْرِجُوهُنَّ مِنۢ بُيُوتِهِنَّ وَلَا يَخْرُجْنَ إِلَّآ أَن يَأْتِينَ بِفَـٰحِشَةٍ مُّبَيِّنَةٍ ۚ وَتِلْكَ حُدُودُ ٱللَّهِ ۚ وَمَن يَتَعَدَّ حُدُودَ ٱللَّهِ فَقَدْ ظَلَمَ نَفْسَهُۥ ۚ لَا تَدْرِى لَعَلَّ ٱللَّهَ يُحْدِثُ بَعْدَ ذَٰلِكَ أَمْرًا ﴿١﴾

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya kai wannan Annabi, (ka ce da jama'arka): "Idan za ku saki mata sai ku sake su a farkon iddarsu, ku kuma kula da ƙidaya idda; kuma ku kiyaye dokokin Ubangijinku; kada ku fitar da su daga ɗakunansu, su ma kada su fita sai dai idan sun aikata alfasha bayayyananna. Waɗannan kuwa su ne iyakokin Allah. Wanda kuwa duk ya ƙetare iyakokin Allah, to haƙiƙa ya zalunci kansa. Ba ka sani ba ko Allah zai farar da wani al'amari bayan wannan.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da kiran Annabi (ﷺ) ya ba shi umarni shi da al'ummarsa cewa, idan suka tashi sakin matansu na aure to su sake su a farkon iddarsu, watau lokacin da suka yi tsarkin haila wanda kuma ba su sadu da su ba a cikinsa, sannan ya umarce su da su kula da ƙidayar kwanakin iddar, domin su iya dawo da matansu kafin ƙarewarta idan suna da buƙatar yin haka. Ya kuma umarce su da su kiyaye dokokinsa, su yi aiki da umarninsa, su kuma guji haninsa.

An karɓo daga Abdurrahman ɗan Aiman ya ce: Na tambayi Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) cewa: "Me kake gani game da mutumin da ya saki matarsa tana haila?" Sai ya ce: "Ibnu Umar ya saki matarsa tana haila a zamanin Manzon Allah (ﷺ), sai Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya tambayi Manzon Allah a kan haka, ya ce masa: Abdullahi ɗan Umar ya saki matarsa tana haila", sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Lalle ya dawo da ita". Sai ya dawo da ita. Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: "Idan ta yi tsarki to yana iya ya sake ta, ko ya riƙe ta." Ibn Umar ya ce: Sai Annabi (ﷺ) ya karanta wannan ayar. [Muslim #1471].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) cewa, ya saki matarsa tana al'ada a zamanin Annabi (ﷺ), sai Umar ɗan Khaɗɗabi (Allah ya ƙara masa yarda) ya yi wa Annabi (ﷺ) tambaya a kan haka. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ka umarce shi ya dawo da ita, sannan ya riƙe ta har sai ta yi tsarki, sannan ta yi haila, sannan ta yi wani tsarkin, sannan idan ya ga dama sai ya riƙe ta, idan kuma ya ga dama sai ya sake ta tun gabanin ya kusance ta, to wannan ita ce iddar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni a saki mata a cikinta." [Bukhari #5251 da Muslim #1471].

Sannan lokacin da matan da suka saki suke zaune a gidajensu suna yin idda, to kada su fitar da su daga gidajensu, su ma kuma matan kada su fice da kansu har sai sun gama iddarsu. Amma wannan da sharaɗin kada su matayen su zo da wani mummunan aiki a gidajen, watau kamar zina ko cin mutuncin mutanen gidan, to idan haka ya faru ya halatta a kore su ko a fitar da su, don tsayar musu da hukuncin Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi gargaɗi da cewa waɗannan hukunce-hukunce da ya bayyana musu iyakokin Allah ne, duk kuwa wanda ya kuskura ya tsallake iyakokinsa, to lalle ya cuci kansa, domin ya jefa kansa cikin hushin Allah da azabarsa. Kuma Allah ya bayyana musu hikimar da ta sa ya hana su fitar da matansu da suka saki daga gidajensu, ko su matan su fice da kansu da cewa, mai yiwuwa ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake kawo jituwa a tsakanin mijin da matar, su fahimci matsalolinsu, su mayar da aurensu ya ci gaba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin kyautata wa mace a kowane hali, a lokacin rabuwa da ita ne ko a lokacin ci gaba da zaman aure tare da ita.

2. Muhimmancin kafa shaidu biyu adalai lokacin saki da lokacin kome, don guje wa rigingimu, kamar ta yi da'awar ita matarsa ce bayan ya mutu, ko 'ya'yansa su yi iƙirarin cewa ubansu ya riga ya sake ta tun kafin ya mutu don haka ba ta da gadonsa, ko ta musunta cewa, mijinta ya dawo da ita don tana son ƙare iddarta, ta auri wani ba shi ba, ko kuma don kore zargi da surutun mutane.

3. An kwaɗaitar da mutane da su riƙa tsayar da shaida don Allah, domin zai iya zamantowa akwai wahala gare su su bar al’amuransu don zuwa bayar da shaida, ko kuma domin nisan wurin bayar da shaidar, ko wani dalili da zai sha musu kai, sai Musulunci ya kwaɗaitar da su cewa, su yi komai don Allah, saboda su samu yardarsa da lada a wurinsa.

4. Babu wanda yake amfana da wa’azi da tunatarwa kamar mutumin da ya yi imani da Allah da ranar lahira.

5. Duk wanda ya kiyaye dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi aiki don neman yardarsa, to lalle Allah zai yi masa kyakkyawar sakayya a duniya da lahira. Daga cikin sakamakon da zai yi masa shi ne, ya samar masa mafita daga duk wani runtsi da damuwa. Wanda kuwa ya ƙi bin dokokin Allah to dole ya yi ta gamuwa da matsaloli iri-iri a rayuwarsa ta duniya, sannan ya gamu da mummunan sakamako a lahira in ya mutu bai tuba ba.

6. Taƙawa, watau kiyaye dokokin Allah, tana daga cikin hanyoyin samun arziki daga Allah.

7. Dogaro ga Allah jari ne babba ga bawa wanda babu abin da ya kai shi.

8. Wajibi ne mumini ya ba da gaskiya da cewa, komai a wurin Allah yana da lokacinsa da iyakarsa, don haka kada ya bari baƙin ciki ya kashe shi, don ya rasa wani abu da yake so, komai yana da lokacinsa a wurin Allah.

Suratuɗ Ɗalaƙ (2-3)
فَإِذَا بَلَغۡنَ أَجَلَهُنَّ فَأَمۡسِكُوهُنَّ بِمَعۡرُوفٍ أَوۡ فَارِقُوهُنَّ بِمَعۡرُوفٖ وَأَشۡهِدُواْ ذَوَيۡ عَدۡلٖ مِّنكُمۡ وَأَقِيمُواْ ٱلشَّهَٰدَةَ لِلَّهِۚ ذَٰلِكُمۡ يُوعَظُ بِهِۦ مَن كَانَ يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّهُۥ مَخۡرَجٗا ۝٢ وَيَرۡزُقۡهُ مِنۡ حَيۡثُ لَا يَحۡتَسِبُۚ وَمَن يَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِ فَهُوَ حَسۡبُهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ بَٰلِغُ أَمۡرِهِۦۚ قَدۡ جَعَلَ ٱللَّهُ لِكُلِّ شَيۡءٖ قَدۡرٗا ۝٣

2. Idan kuma sun kusa isa ƙarshen iddarsu, to ku riƙe su da kyautatawa (ku yi kome), ko kuma ku rabu da su da kyautatawa, kuma ku kafa shaidar adilai guda biyu daga cikinku, ku kuma tsayar da shaidarku saboda Allah. Wannan shi ne ake yin wa’azi da shi ga wanda ya kasance yana yin imani da Allah da ranar lahira. Wanda kuma ya kiyaye dokokin Allah to zai sanya masa mafita.

3. Ya kuma arzuta shi ta inda ba ya tsammani. Duk wanda kuma ya dogara ga Allah to Shi Ya ishe shi. Lalle Allah Mai zartar da al'amarinsa ne. Haƙiƙa kuma Allah Ya sanya iyaka ga kowane abu.

A waɗannan ayoyi kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da sanar da muminai hukunce-hukuncen saki da kome, da jan hankalinsu a kan su kiyaye dokokinsa don su sami mafita a cikin al’amuransu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, idan matan da suka yi wa saki na ɗaya ko na biyu suka kusa gama iddarsu, to suna da ɗayan zaɓi guda biyu:

1. Ko dai su yi musu kome idan suna son su riƙe su da kyautatawa da mutuntawa da kulawa da haƙƙoƙinsu.

2. Ko kuma su rabu da su har su ƙare iddarsu ba tare da tsangwama ko matsanta musu ba, tare kuma da ba su cikakakkun haƙƙoƙinsu, ko ma su kyautata musu da wani abin ihsani don rage musu zafin raɗaɗin rabuwa da kuma surutan mutane.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi umarni idan maza za su yi kome ko za su rabu da matansu to su kafa shaidu biyu adalai a kan sakin ko komen, domin kauce wa duk wani saɓani ko rikici a gaba. Sannan ya umarci su ma masu bayar da shaida da su tsayar da shaidarsu a kan gaskiya tare da neman yardar Allah, watau kada su rage ko su ƙara a kan abin da suka sani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa muminai cewa, waɗannan hukunce-hukunce da iyakoki da yake bayyana musu, yana yin haka ne don su zamanto wa'azi ga wanda ya yi imani da Allah da ranar alƙiyama, domin shi ne kawai wanda zai amfana da tunatarwa da wa'azi. Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu alƙawari da cewa, duk wanda ya tsare dokokinsa, ya yi aiki da umarninsa ya guje wa haninsa, to lalle zai sanya masa mafita daga duk wani ƙunci ko damuwa da zai faɗa cikinta, kuma zai arzuta shi ta inda ba ya tsammani. Don haka mumini ya ci gaba da dogaro ga Allah da mayar da al'amuransa a gare shi, domin ya yi alƙawarin cewa, duk wanda ya dogara gare shi cikin al'amuransa, to shi ya ishe shi ga komai, kuma Allah shi ne mai zartar da al'amarinsa yadda ya ga dama, babu mai iya hana shi, ko wani abu ya gagare shi. Allah ya riga ya sanya wa komai iyaka da yake tuƙewa zuwa gare ta, don haka tsanani yana da iyaka, jin daɗi ma yana da iyaka, babu wani abu mai dawwama har abada a nan duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hukunce-hukuncen iddar mata waɗanda ba sa al'ada saboda manyanta ko kuma ƙanƙanta ko wata lalura da ta sanya jinin hailarsu ya yanke, da kuma iddar mace mai ciki. Amma matar da aka sake ta bayan ta tare tana kuma yin jinin al'ada, to ita iddarta jini uku ne kamar yadda ya zo a '*Suratul Baƙara'*,aya ta 228. Wadda kuma aka sake ta kafin tarewarta da mijinta, to babu wata idda a kanta, kamar yadda ya zo a cikin '*Suratul Ahzab'*,aya ta 49.

2. Hukunce-hukuncen saki da kome da idda wahayi ne daga Allah, ba ya halatta ga wani ya canja su da wani ijtihadinsa har abada.

3. Yana daga cikin amfanin taƙawa ga bawa, samun sauƙi cikin duk al'amuransa da kankare masa laifukansa da ba shi gwaggwaɓan lada a lahira.

Suratuɗ Ɗalaƙ (4-5)
وَٱلَّـٰٓـِٔي يَئِسۡنَ مِنَ ٱلۡمَحِيضِ مِن نِّسَآئِكُمۡ إِنِ ٱرۡتَبۡتُمۡ فَعِدَّتُهُنَّ ثَلَٰثَةُ أَشۡهُرٖ وَٱلَّـٰٓـِٔي لَمۡ يَحِضۡنَۚ وَأُوْلَٰتُ ٱلۡأَحۡمَالِ أَجَلُهُنَّ أَن يَضَعۡنَ حَمۡلَهُنَّۚ وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّهُۥ مِنۡ أَمۡرِهِۦ يُسۡرٗا ۝٤ ذَٰلِكَ أَمۡرُ ٱللَّهِ أَنزَلَهُۥٓ إِلَيۡكُمۡۚ وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ يُكَفِّرۡ عَنۡهُ سَيِّـَٔاتِهِۦ وَيُعۡظِمۡ لَهُۥٓ أَجۡرًا ۝٥

4. Waɗanda kuma suka ɗebe ƙauna ta yin al'ada daga matanku, idan kun yi kokwanto, to iddarsu wata uku ne, da kuma waɗanda ba su taɓa yin al'ada ba. Mata masu ciki kuma ƙarewar iddarsu ita ce haife cikinsu. Duk kuma wanda ya kiyaye dokokin Allah, to zai sanya masa sauƙi game da al'amarinsa

5. Wannan shi ne hukuncin Allah da Ya saukar da shi a gare ku. Duk kuma wanda ya kiyaye dokokin Allah, to zai kankare masa zunubbansa Ya kuma girmama masa lada.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana iddar wasu nau'ikan mata guda uku:
Na ɗaya,matan da suka manyanta har suka cire tsammani daga yin jinin haila, idan ana tantama game da iddarsu, to iddarsu wata uku ne cur.
Na biyu,yara mata ƙanana waɗanda ba su fara yin jinin haila ba, to su ma iddarsu ta saki wata uku ne cikakku.

Na uku, su ne matan da aka sake su ko mazajensu suka rasu suka bar su da ciki, to iddarsu ita ce su haife abin da yake cikinsu, da zarar ta haihu to ta fita daga idda ko takaba ke nan.

An karƁo daga Ummu Salama (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: An kashe mijin Subai'atul Aslamiyya alhalin tana da ciki, sai ta haihu bayan mutuwarsa da kwana arba'in, sai aka fito neman aurenta, sai Manzon Allah (ﷺ) ya aurar da ita. [Bukhari #4909 da Muslim #1484].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tabbatar wa muminai cewa, duk wanda ya kiyaye dokokinsa, to zai sanya masa sauƙi game da al'amarinsa. Ya kuma bayyana musu cewa, wannan hukunci da ya ambata na saki da kome da idda hukuncin Allah ne da ya saukar musu, don su yi aiki da shi, su kiyaye dokokinsa da ya kafa musu; duk kuwa wanda ya kiyaye dokokin Allah, ya yi aiki da umarninsa ya guje wa haninsa, to zai kankare masa laifukansa, ya kuma ba shi lada mai girma a lahira, shi ne shiga Aljanna da samun jin daɗi na har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajabcin bayar da mazauni ga matar da aka sake ta saki na farko da na biyu, har zuwa ƙarshen iddarta.

2. Haramcin cutar da mace mai idda a gidan mijinta, ko ƙuntata mata ta kowace hanyar ƙuntatawa da har za ta fice ta bar gidan.

3. Bai zama wajibi ba a kan matar da aka sake ta da ciki sai ta shayar da ɗan da ta haifa. Wannan haƙƙi ne da yake kan miji.

4. Umarni ga ma'aurata da suka rabu bayan Allah ya ƙaddara samun ɗa a tsakaninsu da su zamanto masu ba wa juna kyakkyawar shawara game da rayuwar ɗansu da tarbiyyarsa, kada su bari abin da ya faru na rashin jituwa a tsakaninsu ya hana su duba maslahar ɗansu, idan suka yi haka sun cutar da kawunansu, sun kuma cutar da ɗansu wanda bai ji ba bai gani ba.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya ɗora wa mutum sai abin da zai iya, don haka kowane miji an wajabta masa ciyarwa ne gwargwadon wadatarsa ko talaucinsa.

6. Ciyar da iyali da kula da su hanya ce daga cikin hanyoyin fita daga tsananin rayuwa da ƙuncinta.

Suratuɗ Ɗalaƙ (6-7)
أَسۡكِنُوهُنَّ مِنۡ حَيۡثُ سَكَنتُم مِّن وُجۡدِكُمۡ وَلَا تُضَآرُّوهُنَّ لِتُضَيِّقُواْ عَلَيۡهِنَّۚ وَإِن كُنَّ أُوْلَٰتِ حَمۡلٖ فَأَنفِقُواْ عَلَيۡهِنَّ حَتَّىٰ يَضَعۡنَ حَمۡلَهُنَّۚ فَإِنۡ أَرۡضَعۡنَ لَكُمۡ فَـَٔاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ وَأۡتَمِرُواْ بَيۡنَكُم بِمَعۡرُوفٖۖ وَإِن تَعَاسَرۡتُمۡ فَسَتُرۡضِعُ لَهُۥٓ أُخۡرَىٰ ٦ لِيُنفِقۡ ذُو سَعَةٖ مِّن سَعَتِهِۦۖ وَمَن قُدِرَ عَلَيۡهِ رِزۡقُهُۥ فَلۡيُنفِقۡ مِمَّآ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُۚ لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفۡسًا إِلَّا مَآ ءَاتَىٰهَاۚ سَيَجۡعَلُ ٱللَّهُ بَعۡدَ عُسۡرٖ يُسۡرٗا ٧

6. Ku zaunar da su (matayen) a inda kuka zauna daidai da samunku, kada kuma ku cuce su don ku ƙuntata musu. Idan kuwa sun kasance masu ciki to sai ku ciyar da su har sai sun haife cikinsu. Sannan idan sun shayar muku da ('ya'yanku) sai ku ba su ladansu; ku kuma daidaita a tsakaninku ta hanya tagari; idan kuma kuka kasa daidaitawa, to wata mai shayarwar sai ta shayar masa.

7. Mawadaci ya ciyar daidai da wadatarsa; wanda kuwa aka ƙuntata masa arzikinsa, to ya ciyar daidai da abin da Allah Ya ba shi. Allah ba Ya ɗora wa rai sai gwargwadon abin da Ya ba shi. Kuma da sannu Allah zai sanya sauƙi bayan tsanani.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin hukuncin ba wa matan da aka saka saki na farko ko na biyu wurin zama, inda ya umarci mazaje da su ba su wurin zama gwargwadon samunsu, Allah bai ɗora musu abin da ya fi ƙarfinsu ba, kada kuma su cutar da su game da ciyarwa ko ba su matsuguni, don su ƙuntata musu har su sanya su bar gidajen ba don suna so ba.
Sai kuma ya bayyana haƙƙin ciyar da matar da aka saka tana da ciki, ya yi umarni da a ciyar da su har sai sun haife abin da yake cikinsu.
Sannan bayan sun haifi ‘ya’yansu, to idan sun shayar da su, sai mazajensu su biya su ladan shayarwarsu, kuma yana da kyau uban da uwar ɗansa da suka rabu su tattauna game da ladan da zai riƙa biya na shayar da ɗansa ta hanyar da ta dace wadda babu ƙwaruwa ga matar ko mijin a ciki. Idan aka yi rashin dace shi mijin ya matse hannu ya yi rowar ladan da ya kamata ya biya na shayar masa da ɗansa, ita ma kuma ta dage sai an biya ta abin da ta yanka, to sai uban ya nemo wata mai shayarwar da za ta shayar masa da ɗansa.
Sai kuma game da batun ciyarwa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ƙowa za a dubi gwargwadon wadatarsa ko talaucinsa, idan miji mai wadata ne sai ya ciyar da sakakkiyar matarsa da ɗansa gwargwadon wadatarsa, wanda kuma yake mai ƙaramin ƙarfi ne, shi ma sai ya ciyar gwargwadon abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hore masa, domin ba wani mutum da Allah yake ɗora masa abin da ya fi ƙarfinsa. Sannan mutane su sani cewa komai na Allah ne, bayan duk wani tsanani yakan kawo sauƙi, ya hore wa talaka arziki mai yawa da wadata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kawo wannan gargaɗi da jan kunne mai tsanani a nan bayan gama bayani a kan hukunce-hukuncen saki da ƙome da idda da shayarwa da ciyarwa da wasu al’amuran zamantakewar aure, yana nuna girman muhimmancinsu, da nuna cewa dokokin aure da zamantakewar miji da mata babban al’amari ne a wurin Allah; saɓa masa a kansu da canja masa dokokinsa da iyakokinsa, taurin kai ne game da bin umarninsa da na Manzonsa, wanda hakan zai iya jawo wa al’umma hushin Allah da azabarsa, ba ga wanda ya aikata laifin kaɗai ba, a’a, ga duk wani wanda yake da ruwa da tsaki wajen canja hukunce-hukuncen Allah da dokokinsa.

2. Girman haɗarin saɓa wa umarnin Allah da na Manzonsa (ﷺ), domin abu ne da yakan jawo azabar Allah ga bawa.

3. Duk mutum mai lafiyayyen hankali, to hankalinsa zai riƙa jan sa zuwa kiyaye dokokin Allah ne ba zuwa saɓa masa ba, domin babu wani mai hankalin da zai fifita asara a kan riba, ko ya zaɓi wani ɗan jin daɗi kaɗan mai yankewa a kan ni’ima ta har abada.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya danganta saukar da Alƙur’ani ga muminai su kaɗai, duk kuwa da cewa an saukar da shi ne ga mutane baki ɗaya, domin muminai su suka fi ƙowa amfana da abin da ya ƙunsa na wa’azi da karantarwa.

5. Shiga gidan Aljanna yana ga wanda ya yi imani ya kuma yi aiki nagari.

Suratuɗ Ɗalaƙ (8-11)

وَكَأَيِّن مِّن قَرْيَةٍ عَتَتْ عَنْ أَمْرِ رَبِّهَا وَرُسُلِهِۦ فَحَاسَبْنَٰهَا حِسَابًا شَدِيدًا وَعَذَّبْنَٰهَا عَذَابًا نُّكْرًا ﴿٨﴾ فَذَاقَتْ وَبَالَ أَمْرِهَا وَكَانَ عَٰقِبَةُ أَمْرِهَا
خُسْرًا ﴿٩﴾ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُمْ عَذَابًا شَدِيدًا ۖ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ يَٰٓأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ۚ قَدْ أَنزَلَ ٱللَّهُ إِلَيْكُمْ ذِكْرًا ﴿١٠﴾ رَّسُولًا يَتْلُوا۟ عَلَيْكُمْ ءَايَٰتِ
ٱللَّهِ مُبَيِّنَٰتٍ لِّيُخْرِجَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ ۚ وَمَن يُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ وَيَعْمَلْ صَٰلِحًا يُدْخِلْهُ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن
تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۖ قَدْ أَحْسَنَ ٱللَّهُ لَهُۥ رِزْقًا ﴿١١﴾

8. Alƙaryu da dama sun yi wa Ubangijinsu da manzanninsa taurin kai, sai Muka yi musu hisabi mai tsanani, Muka azabtar da su azaba mummuna.

9. Saboda haka su ɗanɗani ƙarshen al'amarinsu, ƙarshen al'amarin nasu kuma ya zama taƀewa.

10. Allah Ya tanadar musu azaba mai tsanani; saboda haka ku kiyaye dokokin Allah ya ku ma'abota hankula waɗanda suka yi imani. Haƙiƙa Allah Ya saukar muku da tunatarwa.

11. (Shi ne) Manzo da yake karanta muku ayoyin Allah bayyanannu, don ya fitar da waɗanda suka yi imani suka kuma yi aiki nagari daga duffai zuwa haske. Duk kuwa wanda ya yi imani da Allah ya kuma yi aiki nagari to zai shigar da shi gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu suna masu dawwama a cikinsu har abada. (Wanda aka yi wa haka kuwa) haƙiƙa Allah Ya kyautata masa arzikinsa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi gargaɗi ne game da bijire wa umarninsa da watsi da hukunce-hukuncensa, inda ya bayyana cewa, alƙaryu da dama waɗanda suka bijire wa bin umarnin Ubangijinsu suka saba wa manzanninsa, ya yi musu hisabi mai tsanani da mummunar azaba a kan miyagun ayyukansu a nan duniya kafin abin da yake jiran su a lahira, don haka suka ɗanɗani uƙubar munanan ayyukansu waɗanda ƙarshensu ya zamanto asara ce ta duniya da lahira. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, ya yi musu tanadin azaba mai tsanani da take jiran su a kan kafircinsu da taurin kansu ga manzanninsa, don haka Allah ya umarci muminai masu hankali waɗanda suka yi imani da shi da Manzonsa (ﷺ) da su kiyaye dokokinsa, su yi aiki da umarninsa, su kuma guje wa munanan ayyuka, kada su yi sake har azabar da ta sauka a kan al'ummun da suka gabace su su ma ta sauka a kansu; kuma su tuna da cewa lalle Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar musu da Alƙur'ani wanda yake tunatar da su mummunan ƙarshen mai saƀon Allah da kyakkyawan ƙarshen mutane nagari. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, wannan tunatarwa kuwa ita ce Alƙur'ani wanda Manzonsa (ﷺ) ya zo yana karanta musu ayoyinsa bayyanannu waɗanda babu wata rikitarwa a cikinsu, domin ya fitar da waɗanda suka yi imani da shi kuma suka yi ayyuka nagari daga duffan ƀata zuwa ga hasken shiriya. Duk kuwa wanda ya yi imani da Allah ya yi kyakkywan aiki, to Allah zai shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, suna masu dawwama a cikinsu har abada. Tabbas duk wannan Allah ya kyautata masa arzikinsa har ya shigar da shi gidan Aljannar da ni'imarta ba mai yankewa ba ce har abada, to wannan ya rabauta.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Imani da Kudurar Allah da faɗin iliminsa abu ne da zai samar wa da bawa nutsuwa a zuciyarsa da yarda da hukuncin mahaliccinsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yin ayyukansa da halittarsa don wata hikima da wata manufa mai girma.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci sammai da ƙasa da abubuwan da ke cikinsu domin bayinsa su san girman Kudurarsa da faɗin iliminsa, su bauta masa bisa cancanta.

4. Shigar da tsoro a zukatan bayin Allah, don su guje wa saɓa wa umarninsa, domin idan ya yi niyyar saukar musu azabarsa babu mai iya ba su kariya, kuma komai da suke aikatawa mai kyau ko mummuna, yana sane da shi, zai kuma yi musu sakayya a kai.

5. Ishara zuwa ga muminai cewa, wanda ya saukar musu da hukunce-hukuncen da aka ambata musu a wannan Sura shi ne Allah wanda iliminsa ya kewaye komai, don haka ya fi kowa sanin maslahohin bayinsa ciki da waje, saboda haka abin da ya shar'anta musu na dokoki maslaha ce gare su.

Suratuɗ Ɗalaƙ (12)

رَّسُولٗا يَتۡلُواْ عَلَيۡكُمۡ ءَايَٰتِ ٱللَّهِ مُبَيِّنَٰتٖ لِّيُخۡرِجَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِۚ وَمَن يُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ وَيَعۡمَلۡ صَٰلِحٗا يُدۡخِلۡهُ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ قَدۡ أَحۡسَنَ ٱللَّهُ لَهُۥ رِزۡقَۢا ١١

12. Allah ne Wanda Ya halicci sammai bakwai, ƙasa ma Ya halicci kwatankwacinsu (watau sammai), umarni yana sauka a tsakaninsu, don ku san cewa, Allah Mai iko ne a kan komai, kuma haƙiƙa Allah iliminsa ya kewaye kowane abu.

A wannan aya ta ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rufe magana a kan dokokinsa da hukunce-hukuncensa na aure da bayanin girman Kudurarsa da faffaɗan iliminsa da cewa, shi ne ya halicci sammai bakwai da ƙassai bakwai kamar adadin sammai. Umarninsa na shari'a da na halitta yana saukowa daga tsakaninsu, kuma ya yi haka ne don bayinsa su san cewa, iliminsa ya kewaye komai, babu wani abu a sama ko a ƙasa da bai san shi ba. Watau idan bayi suka san Allah da mafi kyan sunayensu da mafi ɗaukakar siffofinsa masu tsarki, sai su so shi, su bauta masa, su kula da haƙƙoƙinsa, wannan kuwa shi ne babban maƙasudin halittarsu da saukar musu da shari'u.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ba ya halatta ga wani ya haramta abin da Allah ya halatta masa ko ya halatta abin da ya haramta masa.

2. Shi kansa Manzon Allah (ﷺ) bawan Allah ne wanda ake umartar sa ya bi dokokin Allah kada ya saɓa musu. Don haka babu wani mahaluƙi wanda ya isa ya fi ƙarfin dokar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Dole ne ga magidanci ya san wane kishi ne na mata zai ɗauka da muhimmanci, wanne ne ba zai ba wa muhimmanci ba.

4. Shar'anta wa muminai kaffarar rantsuwarsu idan sun warware ta.

5. Bayanin girman matsayin Annabi (ﷺ) da kariyar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ba shi.

6. Daga cikin kyakkyawar mu'amalar Manzon Allah (ﷺ) ga matansa kasancewarsa ba ya ƙididdige musu dukkan abubuwan da yake zargin su da aikatawa na laifuka; yakan faɗi wasu, ya kawar da kansa daga wasu, don soyayya da ƙaunar juna su ɗore.

7. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya zaɓa wa Manzonsa (ﷺ) sai abin da ya fi kyau da nagarta. Don haka tun da ya bar masa matayensa bai musanya masa su da wasu ba har zuwa ƙarshen rayuwarsa, wannan shi ya ƙara tabbatarwa cewa su nagartattu ne masu kyawawan siffofin da aka ambata, babu kuma waɗanda suka fi su.

66-Suratut Tahrim

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan da ta shahara da shi shi ne *'Suratut Tahrim'*, saboda a cikinta aka yi bayanin cewa, bai kamata Annabi (ﷺ) ya haramta wa kansa abin da Allah bai haramta masa ba.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya* a wurin dukkan malamai. Amma Suyuɗi ya bayyana cewa, Malam Ƙatada yana ganin aya ta 10 zuwa ƙarshen Surar *Makkiyya* ne.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ɗari da biyar (105) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *'Suratul Hujurat '* kafin '*Suratul Jumu'a '*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha biyu ne (12).

5. Sababin Saukarta:
An karƀo daga A'isha (Allah Ya ƙara mata yarda), ta ce: Annabi (ﷺ) ya ƙasance yana shan zuma idan ya je wajen matarsa Zainab 'yar Jahsh, yana kuma jimawa a wurinta, sai na haɗa baki da Hafsa cewa kowannemu idan Manzon Allah (ﷺ) ya shigo ɗakinta ta ce masa: "Ka sha tsumin ƙaron itaciyar farar ƙaya, na ji ƙana warinsa." Sai ya ce: "Ni ban san na sha komai ba sai zuma a ɗakin Zainab 'yar Jahsh, ba kuma zan sake shan ta ba, na yi rantsuwa, kada ki faɗa wa kowa wannan labarin." [Bukhari #4912 da Muslim #1474].

An karƀo daga Anas (Allah Ya ƙara masa yarda) ya ce: "Annabi (ﷺ) yana da kuyanga da ya mayar saɗakarsa, sai A'isha da Hafsa (Allah Ya ƙara mata yarda) suka uzzura masa har sai da ya haramta wa kansa ita, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da ayar farko ta wannan Surar]." [Nasa'i, As-Sunan Al-Kubra #8857].

6. Babban Jigonta:
Tarbiyyar gidan Annabi (ﷺ), don ya zama abin koyi ga sauran gidaje da al'umma baki ɗaya.

7. Daga Cikin Abubawan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Hana Musulmi ya haramta wa kansa abin da Allah ya halatta masa don neman yardar wani.
• Wanda ya yi rantsuwa a kan wani abu sai daga baya ya ga wanda ya fi masa alheri, to ya warware rantsuwarsa, ya yi kaffara ya aikata abin da ya fi zama alheri.
• Koyar da matayen aure cewa su daina matsa wa mazajensu, domin yin haka kan iya jawo ƙosawa da juna da tsana, ko ma ya kai ga rabuwa.
• Jan hankalin mutane game da tarbiyyar iyalansu, don kuƀutar da su daga azabar lahira.

• Ba da misali da wasu mataye biyu waɗanda ba nagari ba da kuma wasu biyu nagari, domin su zama abin izina wa’azi ga mataye muminai.

Suratut Tahrim (1-5)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ لِمَ تُحَرِّمُ مَآ أَحَلَّ ٱللَّهُ لَكَ ۖ تَبۡتَغِي مَرۡضَاتَ أَزۡوَٰجِكَ ۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ١ قَدۡ فَرَضَ ٱللَّهُ لَكُمۡ تَحِلَّةَ أَيۡمَٰنِكُمۡ ۚ وَٱللَّهُ مَوۡلَىٰكُمۡ ۖ
وَهُوَ ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡحَكِيمُ ٢ وَإِذۡ أَسَرَّ ٱلنَّبِيُّ إِلَىٰ بَعۡضِ أَزۡوَٰجِهِۦ حَدِيثٗا فَلَمَّا نَبَّأَتۡ بِهِۦ وَأَظۡهَرَهُ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ عَرَّفَ بَعۡضَهُۥ وَأَعۡرَضَ عَنۢ بَعۡضٖ ۖ فَلَمَّا
نَبَّأَهَا بِهِۦ قَالَتۡ مَنۡ أَنۢبَأَكَ هَٰذَا ۖ قَالَ نَبَّأَنِيَ ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡخَبِيرُ ٣ إِن تَتُوبَآ إِلَى ٱللَّهِ فَقَدۡ صَغَتۡ قُلُوبُكُمَا ۖ وَإِن تَظَٰهَرَا عَلَيۡهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ مَوۡلَىٰهُ
وَجِبۡرِيلُ وَصَٰلِحُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ۖ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ بَعۡدَ ذَٰلِكَ ظَهِيرٌ ٤ عَسَىٰ رَبُّهُۥٓ إِن طَلَّقَكُنَّ أَن يُبۡدِلَهُۥٓ أَزۡوَٰجًا خَيۡرٗا مِّنكُنَّ مُسۡلِمَٰتٖ مُّؤۡمِنَٰتٖ
قَٰنِتَٰتٖ تَٰٓئِبَٰتٍ عَٰبِدَٰتٖ سَٰٓئِحَٰتٖ ثَيِّبَٰتٖ وَأَبۡكَارًا ٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya kai wannan Annabi, don me kake haramta abin da Allah Ya halatta maka; kana neman yardar matanka. Allah kuwa Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

2. Haƙiƙa Allah Ya farlanta muku kaffarar rantse-rantsenku. Allah kuwa (Shi ne) Majiɓincin al’amarinku, Shi ne kuma Masani, Mai hikima.

3. Kuma (ka tuna) lokacin da Annabi ya asirta wani zance ga wata daga matansa, to lokacin da ta ba da labarinsa Allah kuma Ya bayyana masa shi, sai ya sanar da (ita) sashinsa ya kuma kawar da kai ga wani sashi; to yayin da ya ba ta labarinsa sai ta ce: “Wane ne ya ba ka labarin wannan?” Sai ya ce: “Masani Mai zuzzurfan ilimi ne Ya ba ni labarinsa.”

4. Idan (ku biyun) kuka tuba zuwa ga Allah, to haƙiƙa zukatanku sun riga sun karkata; idan kuwa kuka haɗe masa kai, to lalle Allah Shi ne Majiɓincin al’amarinsa, da Jibrilu da salihan muminai; mala’iku ma bayan wannan masu taimakawa ne.

5. Tabbas idan ya sake ku Ubangijinsa zai musanya masa wasu matan fiye da ku (su zama) Musulmi, muminai, masu biyayya, masu tuba, masu bautar Allah, masu azumi, zawarawa da ‘yanmata.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da kiran Annabi (ﷺ) da tambayar sa cewa, me ya sa yake haramta wa kansa abin da Allah ya halarta masa, kamar yin saɗaka da kuyangarsa ko shan zuma, don neman yardar matansa masu nuna tsananin kishi. Amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gafarta masa, domin shi mai gafara ne mai jin ƙai.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa ya shar’anta wa muminai hukuncin warware rantse-rantsensu ta hanyar yin kaffara, idan sun ga cewa aikata abin da suka yi rantsuwa a kan barin sa shi ya fi alheri, ko kuma suka karya rantsuwarsu saboda wani dalili. To su yi kaffara kamar yadda aka yi musu bayani a cikin '*Suratul Ma’ida*', aya ta 89. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, shi ne majiɓincinsu mai taimakon su kuma masanin halayen da suke ciki da abin da ya fi zame musu maslaha a rayuwarsu, kuma mai hikima ne cikin halittarsa da shari’arsa da Kaddararsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya tuna lokacin da ya keɓance matarsa Hafsa ya sanar da ita wani labari, ya kuma umarce ta da kada ta sanar da kowa wannan labarin, amma sai ta sanar da A’isha, sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Manzonsa labarin abin da Hafsa ta yi, sai shi kuma ya sanar da ita sashin abin da ta faɗa, ya ɓoye mata wani sashi don cikar haƙurinsa (ﷺ),

sai ta tambaye shi cewa, wane ne ya faɗa masa wannan labarin? Sai ya bayyana mata cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) masanin sarari da ɓoye mai zuzzurfan ilimi shi ne ya faɗa masa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin A'isha da Hafsa cewa, lalle su tuba zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), domin haƙiƙa zukatansu sun karkata zuwa ga abin da bai dace da su ba, wanda har ya kai ga Manzon Allah (ﷺ) ya haramta wa kansa abin da zuciyarsa take so, don su kuma su ji daɗi; don haka tuba ne ya fi dacewa da su. Amma idan har suka haɗe masa kai a kan abin da yake ƙi, suka ci gaba da irin wannan ɗanyen aiki, to su sani Allah ne majiɓincinsa mai taimakon sa, hakanan Mala'ika Jibirilu da muminai nagari da sauran mala'iku; duka masoyansa ne kuma mataimaka a gare shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da su cewa, tabbas idan har suka yi musabbabin Annabi (ﷺ) ya sake su, to zai musanya masa su da wasu matayen da suka fi su komai, waɗanda kuma za su zamanto masu miƙa wuya ga umarnin Allah, masu imani da Allah da Manzonsa, masu biyayya ga Allah, masu tuba daga laifukansu, masu bautar Ubangijinsu, masu azumi, zawarawa da 'yan mata. Sai dai kuma Annabi (ﷺ) bai sake su ba.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wajibi ne a kan kowane mumini ya kula da tarbiyyar iyalansa, ya ba su ilimi na addini wanda zai tsare su daga faɗawa cikin hushin Allah da azabarsa.

2. Mala'iku suna da ayyuka daban-daban, daga cikinsu akwai masu tsaron wuta waɗanda suka siffantu da kaushin hali da tsanani wajen mu'amalarsu da 'yan wuta.

3. Ɗabi'ar halittar mala'iku ita ce yi wa Allah cikakkiyar biyayya, ba tare da saɓa wa umarninsa ba daidai da ƙiftawar ido.

4. Tuba ta gaskiya ita ce dalilin samun duk wani alheri na duniya da na lahira.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai kunyata Manzonsa (ﷺ) da sahabbansa waɗanda suka yi imani da shi ba a ranar alƙiyama.

6. Duk mai son ya samu haske a ranar alƙiyama, to sai ya bi hasken da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi, watau littafin Allah da sunnar Manzon Allah (ﷺ).

Suratut Tahrim (6-8)
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَأَهۡلِيكُمۡ نَارٗا وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُ عَلَيۡهَا مَلَٰٓئِكَةٌ غِلَاظٞ شِدَادٞ لَّا يَعۡصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمۡ وَيَفۡعَلُونَ مَا يُؤۡمَرُونَ ٦ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَا تَعۡتَذِرُواْ ٱلۡيَوۡمَۖ إِنَّمَا تُجۡزَوۡنَ مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ تُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ تَوۡبَةٗ نَّصُوحًا عَسَىٰ رَبُّكُمۡ أَن يُكَفِّرَ عَنكُمۡ سَيِّـَٔاتِكُمۡ وَيُدۡخِلَكُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ يَوۡمَ لَا يُخۡزِي ٱللَّهُ ٱلنَّبِيَّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥۖ نُورُهُمۡ يَسۡعَىٰ بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَبِأَيۡمَٰنِهِمۡ يَقُولُونَ رَبَّنَآ أَتۡمِمۡ لَنَا نُورَنَا وَٱغۡفِرۡ لَنَآۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٨

6. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kare kawunanku da iyalanku daga wuta (wadda) makamashinta mutane ne da duwatsu, masu kula da ita mala'iku ne masu kaushin hali, masu tsananin gaske, ba sa saɓa wa Allah abin da Ya umarce su, suna kuma aikata abin da ake umartar su.

7. Ya ku waɗanda suka kafirta, kada ku kawo wani hanzari a yau; ana saka muku ne kawai da abin da kuka kasance kuna aikatawa.

8. Ya ku waɗanda suka yi imani, ku tuba zuwa ga Allah tuba na gaskiya, tabbas Ubangijinku zai kankare muku kurakuranku Ya kuma shigar da ku gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, a ranar da Allah ba zai kunyata Manzo da waɗanda suka yi imani tare da shi ba; haskensu yana tafe a gabansu da damansu suna cewa: “Ya Ubangijinmu, Ka sa haskenmu ya ɗore, Ka kuma gafarta mana; lalle Kai Mai iko ne a kan komai.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira muminai ya umarce su da su kare kawunansu da iyalansu daga shiga wuta, watau ta hanyar sanin umarnin Allah don aiki da shi; da haninsa don guje masa da tuba daga laifuffuka da aikata duk abin da zai jawo wa bawa hushin Allah da azabar wutar Jahannama wadda makamashin hura ta shi ne mutane da duwatsu, kuma masu tsaron ta mala’iku ne masu kaushin hali ga 'yan wuta, ƙarfafa ne masu tsanani, ba sa saɓa wa Allah yayin da ya umarce su, kuma da zarar ya ba su umarni suke zartar da umarninsa ba tare da ɓata lokaci ba.
An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah Ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Ku umarci yaro da yin salla idan ya kai shekara bakwai, idan kuma ya kai shekara goma sai ku doke shi a kan barin ta.” [Ahmad #15377 da Abu Dawud #494 da Tirmizi #407].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a ranar alƙiyama za a kira waɗanda suka kafirta a shaida musu cewa, kada ma su ce za su kawo wani hanzari game da kafirci da saɓon Allah da suka aikata a duniya, domin faufau ba za a karɓi hanzarinsu ba, saboda lokacin karɓar hanzari ya riga ya wuce tun a duniya, a nan lahira babu abin da za a saka musu da shi sai abin da suka kasance suna aikatawa a duniya na kafirci da saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ƙaryata manzannin Allah.
Su kuma muminai sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira su ya umarce su da su tuba zuwa ga Allah tuba ta gaskiya, domin da haka ne zai kankare musu laifukansu ya kuma shigar da su gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu a ranar alƙiyama, ranar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai tozarta Annabi da waɗanda suka yi imani da shi ba, za su zo haskensu yana tafiya a gabansu da damansu, har su tsallake Siraɗi, suna addu’a suna roƙon Allah ya cika musu haskensu har zuwa shigarsu Aljanna. Kada su zama kamar munafukai waɗanda haskensu yake disashewa yayin da suka hau Siraɗi. Suka ci gaba da roƙon Allah da ya gafarta musu zunubansu, domin shi mai iko ne a kan komai, don haka yana iya biya musu dukkan buƙatunsu.

Daga wannan ayar za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haɗa tsakanin yaƙi na hujja da ilimi da kuma yaƙi na takobi yana nuna muhimmancinsu, kuma ɗaya ba ya isa ba tare da ɗayan ba.

2. Kafirai da munafukai duk ‘yan wuta ne.

3. Annabi (ﷺ) shi ma bawan Allah ne da yake ƙarƙashin umarnin Allah da haninsa, ba ya da ikon fita daga ƙarƙashin shari’ar Allah.

Suratut Tahrim (9)

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ جَٰهِدِ ٱلْكُفَّارَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ وَٱغْلُظْ عَلَيْهِمْ ۚ وَمَأْوَىٰهُمْ جَهَنَّمُ ۖ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ٩

9. Ya kai wannan Annabi, ka yaƙi kafirai da munafukai, ka kuma tsananta musu. Makomarsu kuma Jahannama ce; makoma kuwa ta munana.

A wannan ayar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi kiran Manzonsa (ﷺ) ya umarce shi da ya yaƙi kafirai da hujjoji da makami, ya kuma yaƙi munafukai da hujjoji, ya kuma tsananta musu a kan haka, ya tsayar musu da hujja da yi musu kyakkyawan wa'azi da rushe ɓarnarsu, da yaƙar duk wanda ya yi taurin kai ya yi ƙoƙarin faɗa da gaskiya ko hana ta yaɗuwa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, kafirai da munafukai duk makomarsu wutar Jahannama ce, kuma lalle wannan makoma tasu ta munana.

Daga wannan aya za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A cikin waɗannan misalai biyu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa idan zukata suka zamanto ba su da wani shiri na karɓar gaskiya da yin imani, wa'azi da gauraya da muminai masu tsoron Allah ba zai amfane su da komai ba, kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misali da matar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da matar Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka rayu a gidan annabci amma zukatansu ba su yi laushi da wa'azi da tunatarwa ba. Hakanan idan zuciya ta kasance mai tsarki ce wadda babu ƙazantar kafirci da munafurci a cikinta, to zamanta tare da kafirai da kusancinta da su ba zai canja mata komai ba, ba za ta tasirantu da ɓatan ɓatattu ko zaluncin azzalumai ba, kamar yadda misalin matar Fir'auna ya nuna; ta kasance a gidan Fir'auna wanda ya tilasta mata karɓar addinin maguzanci da bautarsa amma ta bijire musu, ta yi imani da Allah da Manzonsa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ta kafe a kan haka har lokacin mutuwarta ya zo ta koma ga Ubangijinta tana mai neman mafaka a wurinsa da kyakkyawan sakamako na gidan Aljanna. Hakanan ita ma Maryamu 'yar Imrana wadda ta tsare mutuncinta da matsayinta sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗaukaka matsayinta a duniya da lahira, ta haifi Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ta gaskata dukkan hukunce-hukuncen da shari'a ta zo da shi, ta tabbata cikin mata masu yi wa Allah biyayya.

2. Kusancin mutum ga mutanen kirki, ba zai amfane shi a lahira ba sai in ya yi imani da Allah ya yi kyakkyawan aiki.

3. Kame kai da guje wa tuhuma siffa ce daga cikin siffofin mata muminai nagari.

4. Shiriya da ɓata duk a hannun Allah suke, yana sanya su ga wanda ya ga dama cikin bayinsa. Da a ce shiriya a hannun wani mahaluƙi take da matar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ta Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ba su ɓace sun hallaka ba, da kuma a ce ɓatarwa a hannun wani take da matar Fir'auna ba ta kai labari ba.

5. Addu'ar Asiya matar Fir'auna tana tabbatar da cewa, ita mace ce da ƙyale-ƙyalen duniya ko burgar mulki ba su dame ta ba, don haka babu abin da yake cikin ranta sai roƙon Allah da fatan ya ba ta gidan Aljanna.

Suratut Tahrim (10-12)

ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱمۡرَأَتَ نُوحٖ وَٱمۡرَأَتَ لُوطٖۖ كَانَتَا تَحۡتَ عَبۡدَيۡنِ مِنۡ عِبَادِنَا صَٰلِحَيۡنِ فَخَانَتَاهُمَا فَلَمۡ يُغۡنِيَا عَنۡهُمَا مِنَ ٱللَّهِ شَيۡـٔٗا وَقِيلَ ٱدۡخُلَا ٱلنَّارَ مَعَ ٱلدَّٰخِلِينَ ١٠ وَضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱمۡرَأَتَ فِرۡعَوۡنَ إِذۡ قَالَتۡ رَبِّ ٱبۡنِ لِي عِندَكَ بَيۡتٗا فِي ٱلۡجَنَّةِ وَنَجِّنِي مِن فِرۡعَوۡنَ وَعَمَلِهِۦ وَنَجِّنِي مِنَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ١١ وَمَرۡيَمَ ٱبۡنَتَ عِمۡرَٰنَ ٱلَّتِيٓ أَحۡصَنَتۡ فَرۡجَهَا فَنَفَخۡنَا فِيهِ مِن رُّوحِنَا وَصَدَّقَتۡ بِكَلِمَٰتِ رَبِّهَا وَكُتُبِهِۦ وَكَانَتۡ مِنَ ٱلۡقَٰنِتِينَ ١٢

10. Allah Ya ba da wani misali ga waɗanda suka kafirta da matar Nuhu da matar Luɗu; sun kasance ƙarƙashin (igiyar auren) wasu bayi su biyu salihai daga bayinmu, sai suka ha'ince su, saboda haka ba su wadatar musu komai ba (daga azabar) Allah, aka kuma ce: "Ku shiga wuta tare da masu shiga."

11. Allah kuma Ya ba da wani misali ga waɗanda suka yi imani da matar Fir'auna lokacin da ta ce: "Ya Ubangijina, Ka gina min gida a wurinka cikin Aljanna, Ka kuma tserar da ni daga Fir'auna da aikinsa, kuma Ka tserar da ni daga azzaluman mutane."

12. Da kuma Maryamu 'yar Imrana wadda ta kiyaye matuncinta, sai Muka masa busa daga Ruhinmu, ta kuma gaskata ayoyin Ubangijinta da littattafansa, ta kuma kasance daga masu biyayya ga Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayar da misalai guda biyu:
Na farko, misali ne ga waɗanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa, don su san cewa kusancinsu da alaƙarsu da muminai ba za su amfane su da komai ba a wajen Allah, domin su yi la'akari da matan annabawan nan biyu, watau matar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da matar Annabi Luɗu, sun kasance matayen aure ne a ƙarƙashin bayin Allah nagari, to amma sai suka ha'ince su, watau suka kafirce musu suka riƙa hana mutane bin addininsu, suka kuma riƙa goyon bayan kafirai maƙiyansu, don haka sai kasancewarsu matan annabawa bai amfana musu komai ba, a ranar lahira kuma za a ce musu, su shiga wutar Jahannama tare da kafirai da fasiƙai masu shigar ta.
Misali na biyu, shi ne ga waɗanda suka yi imani da Allah da Manzanninsa, inda ake nuna musu cewa, alaƙarsu ko kusancinsu da kafirai ba zai cutar da su ba matuƙar dai suna tsaye ɗoɗar kan tafarkin Allah madaidaici. Abin la'akari a wajensu shi ne al'amarin matar Fir'auna babban maƙiyin Allah, lokacin da take addu'a tana roƙon Ubangijinta da ya gina mata wani gida a wajensa a Aljanna, ya kuma kuɓutar da ita daga zaluncin Fir'auna da kama-karyarsa da miyagun ayyukansa, ya kuɓutar da ita daga azzaluman mutane masu goyon bayan zaluncin Fir'auna da ta'addancinsa.
Sannan kuma ya ba su misali da Maryamu 'yar Imrana wadda ta tsare matuncinta ta kare farjinta daga aikata zina, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Mala'ika Jibrilu ya yi busa a cikinsa sai ta sami cikin Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Kudurar Allah ba tare da uba ba. Ta kuma gaskata shari'o'in Allah da littattafansa da ya saukar wa manzanninsa, ta zamanto daga cikin masu biyayya ga Allah wajen aikata umarninsa da guje wa haninsa.

An karɓo daga Abu Musa Al-Ash'ari (Allah Ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Maza da yawa sun samu kamala, amma mata ba waɗanda suka samu kamala sai Asiya matar Fir'auna da Maryamu 'yar Imrana da Khadija 'yar Khuwailid. Kuma falalar A'isha a kan sauran mata kamar falalar fatan gurasa da romon nama ne a kan sauran abinci." [Bukhari #3411 da Muslim #2431].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yawaitar albarkatun Allah da alheransa a ko'ina.

2. Tabbatar wa da Allah siffar Hannu yadda ya dace da shi ba tare da kwatanta shi da wani mahaluƙi ba ko yi wa siffar wani tawili.

3. Gamewar Kudurarsa ga kowa da komai.

4. Hikimar halittar mutuwa da rayuwa, watau shi ne don bawa ya yi gaggawa wajen aikin alheri tun mutuwa ba ta riske shi ba.

5. Abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake so daga bayinsa shi ne kyautata ayyukansu ba yawaita su ba, domin duk yawan aiki idan ba shi da kyau ba zai amfanar da bawa ba sai dai ya cutar da shi.

6. Kyakkyawan aiki a wurin Allah shi ne wanda aka yi dominsa, kuma ya dace da koyarwar shari'arsa. Fudhailu ɗan Iyadh yana cewa: "Lalle aiki idan ya zamanto da ikhlasi a cikinsa, watau an yi shi don Allah kaɗai, amma bai zama daidai ba, watau bai dace da umarnin shari'a ba, to ba za a karɓe shi ba. Hakanan idan ya zamanto daidai amma babu ikhlasi a cikinsa, shi ma ba za a karɓa ba, har sai ya zamanto an yi shi da ikhlasi ya kuma dace da shari'a. Mai ikhlasi shi ne wanda aka yi don Allah; daidai kuwa shi ne idan ya kasance a kan Sunna". [Dubi, Ibnu Abid Dunya, *Al-Ikhlas Wan-Niyya*, #22].

7. Sammai hawa-hawa ne wata a kan wata kamar rufi ba tare da suna gugar juna ba.

8. Sama a haɗe take babu tsattsagewa ko ɓaraka a jikinta. Mala'iku suna hawa da sauka daga ƙofofin da Allah ya sanya mata, babu wanda ya san yadda suke ko ya san adadinsu sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

9. Hikimar halittar taurari a sararin samaniya, shi ne domin su zama fitilu masu haskaka ƙasa, su kuma zama ado a sararin sama, da su mutane suke gane hanya ko mafuskanta, sannan su zama ababen jifan shaiɗanu masu hawa sama don satar sauraron maganganun mala'iku.

10. Tabbatar da samuwar shaiɗanu waɗanda su halitta ne masu zaman kansu, saɓanin masu cewa, shaiɗanu wani ƙarfi ne na sharri tare da mutum.

11. An riga an halicci wuta an tanade ta tana nan a halin yanzu.

67-Suratul Mulk

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan da ta shahara da shi shi ne *'Suratul Mulk*'. Tana da wasu sunaye daban kamar, *'Suratu Tabarakal Mulk*' da *'Suratu Tabarakal Lazi Biyadihil Mulk'*.
An sa mata sunan ne da kalmomin farko da suka zo a cikinta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin yawancin malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta saba'in da shida (76) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *'Suratul Mu'uminuna'* kafin '*Suratul Haƙƙa*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta talatin ne (30), amma a lissafin mutanen Hijaz talatin da ɗaya ne (31).

5. Falalarta:
An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle akwai wata Sura a cikin littafin Allah mai ayoyi talatin, ta yi wa wani mutum ceto a wurin Allah har sai da aka gafarta masa." [Ahmad #7975 da Abu Dawud #1400 da Tirmizi #3111 da Ibn Maja #3786].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "*Suratu Tabaraka* ita ce mai hana azabar ƙabari." [Dubi Al-Bani, *Assahiha* #1140].

6. Babban Jigonta:
Tana karantar da sanin Kudurar Allah da cikar mulkinsa da faffaɗan iliminsa, don cusa wa mutane girmama Allah da tsoron azabarsa.

7. Daga Cikin Abubawan Da Ta Kunsa Akwai:
• Sanar da muminai girman mulkin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da jan hankalinsu a kan su lura da manyan halittunsa masu nuna cikakkiyar hikimarsa da gwanintarsa.
• Faɗakarwa game da hikimar halittar rayuwa da mutuwa, watau don jarraba ayyukan mutane a gane masu kyawawan ayyuka da masu munanan ayyuka.
• Gargaɗin mutane game da makircin shaiɗanu da guje wa aukawa wutar Jahannama tare da su.
• Faɗakar da mutane game da cewa, tsira daga azabar Jahannama ta tattaru ne a cikin bin Manzon Allah (ﷺ), asara kuwa tana tare da ƙaryata shi.
• Tunatar da mutane baiwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu, ta halittar sammai da ƙasa da ni'imomin da ya sanya a cikinsu, domin amfanin su mutane.

• Tsoratar da mutane cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana da ikon ya rushe tsarin tafiyar sama da ƙasa, sai mutane su wayi gari cikin ɗimuwa da wahala, amma bai yi haka ba don ya tabbatar musu da ni'imarsa.
• Tsoratar da mushirikai a kan su guji kafirce wa ni'imomin Allah da yin izgili da alƙawarinsa, domin azabarsa kusa take, za kuma ta riske su.

Suratul Mulk (1-5)

تَبَٰرَكَ ٱلَّذِى بِيَدِهِ ٱلْمُلْكُ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ۝١ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلْمَوْتَ وَٱلْحَيَوٰةَ لِيَبْلُوَكُمْ أَيُّكُمْ أَحْسَنُ عَمَلًا ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْغَفُورُ ۝٢ ٱلَّذِى
خَلَقَ سَبْعَ سَمَٰوَٰتٍ طِبَاقًا ۖ مَّا تَرَىٰ فِى خَلْقِ ٱلرَّحْمَٰنِ مِن تَفَٰوُتٍ ۖ فَٱرْجِعِ ٱلْبَصَرَ هَلْ تَرَىٰ مِن فُطُورٍ ۝٣ ثُمَّ ٱرْجِعِ ٱلْبَصَرَ كَرَّتَيْنِ يَنقَلِبْ إِلَيْكَ
ٱلْبَصَرُ خَاسِئًا وَهُوَ حَسِيرٌ ۝٤ وَلَقَدْ زَيَّنَّا ٱلسَّمَآءَ ٱلدُّنْيَا بِمَصَٰبِيحَ وَجَعَلْنَٰهَا رُجُومًا لِّلشَّيَٰطِينِ ۖ وَأَعْتَدْنَا لَهُمْ عَذَابَ ٱلسَّعِيرِ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Wanda mulki yake a hannunsa alhairansa sun yawaita, kuma Shi Mai iko ne a kan komai.

2. Wanda Ya halicci mutuwa da rayuwa don Ya jarraba ku (Ya bayyana) wane ne a cikinku ya fi kyakkyawan aiki? Shi kuma Mabuwayi ne, Mai gafara.

3. Wanda Ya halicci sammai bakwai hawa-hawa; ba za ka ga wata tangarɗa cikin halittar (Allah) Mai rahama ba. Ka maimaita dubanka, shin za ka ga wata tsaga?

4. Sannan ka sake mayar da gani sau da yawa, ganin zai dawo maka a ƙasƙance, shi kuma yana a dakushe (bai ga wata tsaga ba).

5. Kuma haƙiƙa Mun ƙawata saman duniya da taurari Muka sanya su kuma ababan jifan shaiɗanu; Muka kuma tanadar musu azabar (wutar) Sa'ira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da yi wa kansa kirari da cewa shi ne wanda mulkin komai yake a hannunsa albarkatunsa da alheransa kuma sun yawaita sun mamaye ko'ina da ina a sama da ƙasa, kuma shi mai iko ne a kan komai, babu wani abu da yake gagarar sa ko yake fita daga ƙarƙashin ikonsa. Sannan ya bayyana wasu dalilai na Kudurarsa da cewa, shi ne wanda ya halicci mutuwa da rayuwa, ya ƙaddara za su faru ga bayinsa, don ya jarrabe su ya bayyana wane ne a cikinsu ya fi kyakkyawan aiki. Kuma shi Mabuwayi ne wanda babu mai rinjayar sa, kuma mai gafara ne ga bayinsa masu laifi idan su tuba.
Hakanan daga cikin dalilan Kudurarsa da ikonsa, shi ne wanda ya halicci sammai bakwai hawa-hawa, watau wata a saman wata da tazara tsakanin kowace sama da 'yar'uwarta, ya kuma inganta halittarsu ta yadda mutum ba zai iya ganin wata tangarɗa ko zoɓawa ba a tare da su, duk kuwa yadda mutum ya kai ga naci da ƙura ido ba zai taɓa ganin wata ɓaraka ba a jikinsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya sake umartar mutum ya sake ƙura idanunsa sosai ko zai ga wata tawaya a halittar sammai, Allah ya tabbatar da cewa, hakanan zai yi har ya gaji ba tare da ya ga wani abin kushewa ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin kyau da ƙaye da sama take da shi, domin ya ƙawata ta da taurari masu haske kamar fitilu da daddare, sannan ya mayar da su harshen wuta na jifan shaiɗanu masu ƙoƙarin satar ji su ƙona su, a lahira kuwa ya tanadar musu azabar wutar Jahannama, saboda kafircin da suke yi da kuma jefa bayinsa cikin ɓata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoratar da kafirai azabar wutar Jahannama.

2. Kafirai a ranar alƙiyama za su gamu da wulaƙanci, domin za a riƙa jefa su cikin wuta kamar ana jefa gumagumai, saɓanin ‘yan Aljanna waɗanda za a umarce su da shiga Aljanna cikin mutuntawa da girmamawa.

3. Wutar Jahannama za ta nuna tsananin marmarinta ga kafirai, saboda haka za ta riƙa hargagi tana gunji da tafarfasa.

4. Za a jefa kafirai cikin wutar Jahannama ƙungiya-ƙungiya, ƙowannensu za a haɗa shi da ‘yan’uwansa masu laifuka iri ɗaya.

5. Wuta tana da mala’iku masu tsaron ta.

6. Babu wanda zai shiga wuta sai wanda hujja ta tabbata a kansa.

7. Wutar lahira ba irin ta duniya ce ba, shi ya sa duk wanda ya shige ta ba zai daina ji da gani da magana ba, kamar yadda yake faruwa ga wanda ya shiga wutar duniya, wanda shi zai rasa jinsa da ganinsa, zai kasa ci gaba da maganganu ko amsa tambayoyi.

8. Kafirai a lahira za su yi nadama amma nadamarsu ba za ta amfana musu ƙomai ba sai ƙarin baƙin ciki.

9. Kafirai sun yi watsi da hankalin da Allah ya ba su don su fahimci gaskiya su karɓe ta, don haka ne suka dulmiya cikin kafirci da ɓata.

10. Miƙa wuya ga hujjojin Allah ne kawai zai tsare bawa daga aukawa cikin azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Mulk (6-11)
وَلِلَّذِينَ كَفَرُواْ بِرَبِّهِمۡ عَذَابُ جَهَنَّمَۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ٦ إِذَآ أُلۡقُواْ فِيهَا سَمِعُواْ لَهَا شَهِيقٗا وَهِيَ تَفُورُ ٧ تَكَادُ تَمَيَّزُ مِنَ ٱلۡغَيۡظِۖ كُلَّمَآ أُلۡقِيَ فِيهَا
فَوۡجٞ سَأَلَهُمۡ خَزَنَتُهَآ أَلَمۡ يَأۡتِكُمۡ نَذِيرٞ ٨ قَالُواْ بَلَىٰ قَدۡ جَآءَنَا نَذِيرٞ فَكَذَّبۡنَا وَقُلۡنَا مَا نَزَّلَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٍ إِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ كَبِيرٖ ٩ وَقَالُواْ
لَوۡ كُنَّا نَسۡمَعُ أَوۡ نَعۡقِلُ مَا كُنَّا فِيٓ أَصۡحَٰبِ ٱلسَّعِيرِ ١٠ فَٱعۡتَرَفُواْ بِذَنۢبِهِمۡ فَسُحۡقٗا لِّأَصۡحَٰبِ ٱلسَّعِيرِ ١١

6. Waɗanda kuma suka kafirce wa Ubangijinsu suna da azabar Jahannama; makoma kuwa ta munana.

7. Idan aka jefa su a cikinta sai su ji kururuwarta, tana tafarfasa.

8. Tana kusa da ta kekkece saboda tsananin fushi; duk sanda aka jefa wata tawaga a cikinta sai masu tsaron ta su tambaye su: “Shin mai gargaɗi bai zo muku ba?”

9. Sai su ce, “E, haka ne, haƙiƙa mai gargaɗi ya zo mana, sai muka ƙaryata, muka kuma ce, Allah bai saukar da wani abu ba, ba kwa a kan komai sai ɓata mai girma.”

10. Suka kuma ce: “Da mun kasance muna fahimta ko kuma muna hankalta, to da ba mu kasance cikin ‘yan (wutar) Sa’ira ba.”

11. Sai suka amsa laifinsu, sai (a ce da su): “Can dai da ‘yan (wutar) Sa’ira.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan halin da kafirai za su tsinci kansu a cikinsa a ranar alƙiyama, inda ya tabbatar musu cewa, wutar Jahannama mai ruruwa tana jiran su ranar alƙiyama, ita ce makomarsu ta ƙarshe, wannan makoma tasu kuwa ta munana matuƙa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yayin da za a jefa su cikin wutar Jahannama za su ji tana hargagi da sauti mai ɗaga hankali tana tafarfasa, kamar za ta tsage don tsananin hushi da duk wani wanda za a jefa shi cikinta. Kuma duk sanda aka jefa wata ƙungiya ta kafirai a cikinta sai mala'iku masu tsaron ta su tambaye su cikin zargi da tuhuma cewa, shin ba wani mai gargaɗi da ya zo musu yana tsoratar da su azabar Allah? Sai kafirai su amsa musu da cewa, e, lalle manzo mai gargaɗi ya zo musu ya kuma tsoratar da su azabar Allah, to amma sai taurin kansu ya sanya suka ƙaryata shi har ma suka faɗa masa cewa, babu wani wahayi da aka yi masa, suka zargi manzannin Allah da cewa, ba a kan komai suke ba sai ɓata mai girma.
Sannan sai kafirai 'yan wuta suka ci gaba da zargin kansu da nadama a lokacin da nadama ba za ta amfana musu komai ba, suna faɗar cewa, da a ce sun ƙasance masu sauraro irin na basira ko sun yi aiki da hankalinsu, sun tsaya sun nutsu sun bambance tsakanin ƙarya da gaskiya, da ba su tsinci kansu cikin 'yan wuta ba, domin da sun yi imani da manzannin Allah sun gaskata abin da suka zo da shi na gaskiya, to da sun zama 'yan Aljanna. Don haka sai suka yi iƙirari da laifinsu da bakinsu, suka tabbatar cewa sun yi kafirci sun ƙaryata manzannin Allah, don haka sun cancanci shiga wutar Jahannama. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tir da 'yan wuta ya nesanta su daga rahamarsa.

An karɓo daga Abul Bakhtari Aɗ-Ɗa'i ya ce, wani wanda ya ji wannan hadisi daga Manzon Allah ya faɗa min cewa, Annabi (ﷺ) ya ce: "Ba za a hallakar da mutane ba har sai su da kansu sun yanke wa kansu hanzari." [Ahmad #28342 da Abu Dawud #4347].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoron Allah a ɓoye yana daga cikin dalilan samun gafarar Allah da lada mai girma, watau gidan Aljanna.

2. Mai tsoron Allah na gaskiya shi ne wanda yake kiyaye dokokinsa a bayan idon mutane kamar yadda yake yi a gabansu.

3. Tsoron Allah a bayan idon mutane alama ce ta ikhlasi, watau yi don Allah.

4. Faffaɗan ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya game abin da aka ɓoye da wanda aka bayyana duk daidai ne a wurinsa, ya san komai sarai.

5. Jan hankali ga mutane a kan su gyara zukatansu, su sanya niyyar alheri a cikinsu koyaushe, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san duk abin da suke ɓoyewa a ransu tun ma kafin su furta ko su aikata.

6. Duk wanda ya yarda da cewa Allah shi ne mahaliccin komai, to dole ne ya amince da cewa ya san komai na sarari da na ɓoye.

7. Aiki da hankali shi ne yarda da dokokin Allah da shari'arsa da fifita ta a kan duk wani tsari da doka ta ɗan'adam, domin shi ne mahaliccin kowa da komai. Wanda kuwa ya yi halitta shi ne ya fi sanin abin da zai dace da maslahar abin da ya halitta, don haka Allah ne ya fi sanin maslahar bayinsa, wannan ne ya sa ya aiko da manzanni ya saukar da littattafai, don ɗora ɗan'adam a kan tafarki madaidaici.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta ƙasa wadda ɗan'adam da sauran halittu suke rayuwa a kanta da horarriyar dabba, kamar doki da ɗan'adam yake hawa yana sukuwa a kansa cikin nutsuwa da kwanciyar hankali, ba tare da tsoron zai yi tutsu da shi ya jefar da shi ƙasa ba. Hakanan ita ma wannan ƙasa da mutane suke rayuwa a kanta, duk da cewa tana zagaya kanta, tana kuma zagaya rana a gurguje, amma kuma ɗan'adam yana rayuwarsa a bayanta cikin natsuwa da kwanciyar hankali ba tare da yana jin wani tangal-tangal ba, ba kuma tare da yana jin tsoron ta yi tutsu ta jefar da shi ba. Wannan gagarumar ni'imar Allah ce wadda take nuna isar Kudurarsa da ikonsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai ba tare da wani abokin tarayya ba.

9. Daga cikin hore ƙasa da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan'adam shi ne, yadda ya ba shi damar noma a kanta da haƙa rijiyoyin ruwa da gudanar da idanuwan ruwa da buɗe hanoyin da mutane suke zirga-zirga a kansu da binne mutane a cikinta.

10. Umarni ga ɗan'adam a kan ya fita neman abincinsa kada ya zauna ya dogara da abin da mutane za su ɗauka su ba shi.

11. Tafiye-tafiye a bayan ƙasa yana daga cikin hanyoyin samun arziki.

Suratul Mulk (12-15)

إِنَّ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُم بِٱلۡغَيۡبِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٞ كَبِيرٞ ١٢ وَأَسِرُّواْ قَوۡلَكُمۡ أَوِ ٱجۡهَرُواْ بِهِۦٓۖ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ١٣ أَلَا يَعۡلَمُ مَنۡ خَلَقَ وَهُوَ ٱللَّطِيفُ ٱلۡخَبِيرُ ١٤ هُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ ذَلُولٗا فَٱمۡشُواْ فِي مَنَاكِبِهَا وَكُلُواْ مِن رِّزۡقِهِۦۖ وَإِلَيۡهِ ٱلنُّشُورُ ١٥

12. Lalle waɗanda suke tsoron Ubangijinsu ba tare da suna ganin sa ba, suna da gafara da kuma lada mai girma.

13. Da ku ɓoye zancenku ko ku bayyana shi, lalle Shi Masanin abin da yake cikin zukata ne.

14. Yanzu wanda ya yi halitta ba zai san ta ba? Shi ne kuma Mai tausasawa Masani.

15. Shi ne wanda Ya sanya muku ƙasa horarriya, saboda haka ku yi tafiya a cikin sasanninta kuma ku ci daga arzikinta; makoma kuwa zuwa gare Shi take.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa muminai masu tsoron sa a lokacin da suka kaɗaita da kawunansu cewa, suna da gafarar zunubansu, kuma suna da wani lada mai girma, ita ce Aljanna. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutane cewa, da su ɓoye zancensu ko su bayyana shi a fili duk daidai suke a wurinsa, domin shi masanin abin da yake cikin zukatan bayinsa ne, babu abin da zai ɓuya a gare shi. Domin kuwa ba zai yiwu a ce wanda ya ƙagi halitta ya kasa sanin sirrin waɗannan halittu nasa ba, alhalin shi mai tausasa wa bayinsa ne, masanin dukkan al'amuransu ne, babu abin da yake ɓuya a gare shi.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa bayinsa wata babbar ni'ima da ya yi musu ta hore musu bayan ƙasa har ta zamanto mai sauƙin zama da rayuwa a kanta, ba tare da tana tangal-tangal da su ba, don haka ya umarce su da su yi tafiye-tafiyensu a cikin sassanta da ɓangarorinta domin neman arziki da ya sanya a ko'ina a cikinta, kuma su ci daga wannan arzikin nasa wanda ya tanade shi saboda su, su kuma yi wa kansu kyakkyawan shiri na haɗuwa da shi, don kuwa makomarsu gaba ɗaya zuwa gare shi ne, domin yi musu hisabi da sakamako.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da ɗaukakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a sama da halittarsa, ɗaukaka ta Zati da sifa da iko.

2. Imani da ɗaukakar Allah a sama, wani abu ne da yake tattare da asalin halittar ɗan'adam, hatta mushirikai ma sun san haka, kuma sun yi imani da shi.

3. Yana daga cikin abin da yake sanya kafirai dogewa a kan kafircinsu, amincewa da cewa azabar Allah ba za ta taɓa samun su ba.

4. Tsayuwar ƙasa da rashin yin tangal-tagal yana daga cikin manyan ni'imomin da Allah ya yi wa bayinsa.

5. Tsoratar da kafirai na wannan al'umma da irin azabar Allah da ta sauka a kan kafiran da suka gabace su.

6. Tashin tsuntsaye a sama da saukarsu yana daga cikin manyan ayoyin Allah masu nuna cikar Kudurarsa, amma da yawa daga cikin mutane ba sa lura da haka. Wannan ayar ta ƙunshi har tashin jiragen sama a cikin sararin samaniya ɗauke da mutane da kayayyaki masu nauyi babu abin da yake riƙe su sai Allah da rahamarsa da luɗufinsa.

Suratul Mulk (16-19)
ءَأَمِنتُم مَّن فِي ٱلسَّمَآءِ أَن يَخۡسِفَ بِكُمُ ٱلۡأَرۡضَ فَإِذَا هِيَ تَمُورُ ١٦ أَمۡ أَمِنتُم مَّن فِي ٱلسَّمَآءِ أَن يُرۡسِلَ عَلَيۡكُمۡ حَاصِبٗاۖ فَسَتَعۡلَمُونَ كَيۡفَ نَذِيرِ ١٧ وَلَقَدۡ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ فَكَيۡفَ كَانَ نَكِيرِ ١٨ أَوَ لَمۡ يَرَوۡاْ إِلَى ٱلطَّيۡرِ فَوۡقَهُمۡ صَٰٓفَّٰتٖ وَيَقۡبِضۡنَۚ مَا يُمۡسِكُهُنَّ إِلَّا ٱلرَّحۡمَٰنُۚ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَيۡءِۭ بَصِيرٌ ١٩

16. Yanzu kun amince cewa wanda Yake sama Ya kifar da ƙasa da ku, sai kawai ku gan ta tana ta tambal-tambal?

17. Ko kuma kun amince cewa wanda Yake sama Ya aiko muku da guguwa mai tsakwankwani? To da sannu za ku san yadda (sakamakon) gargaɗina zai zama.

18. Haƙiƙa kuma waɗanda suke gabaninku sun ƙaryata, to yaya (sakamakon) nuna ƙin amincewata ya zama?

19. Shin ba sa ganin tsuntsaye a samansu suna shimfiɗa (fikafikansu) suna kuma rufe su? Ba wanda yake riƙe da su sai (Allah) Mai rahma. Lalle Shi Mai ganin komai ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankulan mutane zuwa ga lura da wasu ayoyi masu nuna girman Kudurarsa da cikar Mulkinsa, tare da tsoratar da su game da saɓa masa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su cewa, yanzu sun amince Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda yake sama cewa ba zai kifar da ƙasa da su ta haɗiye su ba, kamar yadda ya yi wa Karuna, sai kawai su gan ta tana tambal-tambal da su bayan a da suna zaune lafiya a kanta? Ko kuma sun amince da cewa wanda yake sama, watau Allah ba zai aiko musu da duwatsu daga sama ba, kamar yadda ya yi wa mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ruwan duwatsu daga sama ya hallaka su? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya razana su da cewa ba da jimawa ba za su san yadda sakamakon gargaɗinsa zai zama, watau lokacin da za su ga azaba ta nufo su gadan-gadan, a lokacin babu wata nadama da za ta yi musu amfani.

An karɓo daga Mu’awiya ɗan Hakim (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na mari wata baiwata bayan ta yi sakaci har kyarkeci ya cinye min akuyata, sai kuma na yi nadama, na zo da ita wajen Manzon Allah (ﷺ) na ce: Ya Manzon Allah, shin ba na ‘yanta ta ba? Sai Manzon Allah (ﷺ) ya tambaye ta: “Ina Allah yake?” Sai ta ce: “Yana sama.” Sai ya ce mata: “Ni wane ne?” Sai ta ce: “Kai Manzon Allah ne.” Sai ya ce: “Ka ‘yanta ta, domin ita mumina ce.” [Muslim #537 da Abu Dawud #930].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Masu tausayawa, Allah mai rahama yana tausaya musu, ku tausaya wa wanda yake ƙasa sai wanda yake sama ya tausaya muku.” [Abu Dawud #4941 da Tirmizi #1924 da Ahmad #6494].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa mushirikai cewa, al’ummun da suka gabace su sun ƙaryata manzannin Allah, sai azabar Allah ta sauko musu yayin da suka doge a kan kafirci da tsaurin kai, to su duba su ga yadda sakamakon inkarinsa a gare su ya zama, domin ya zama sakamako ne mai tsanani, don haka su ma mushirikai su yi hattara kada su jawo wa kawunansu irin wannan mummunan sakamako a duniya da lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata babbar aya da ke nuna cikar Kudurarsa da ikonsa, yayin da ya tambayi mutane cewa, shin ba su ga yadda tsuntsaye suke tashi cikin sararin sama ba, suna tafiya sahu-sahu cikin natsuwa da walwala, babu mai riƙe su ya hana su faɗowa ƙasa sai Allah Mai rahama? Lalle shi Allah mai ganin komai ne, babu abin da yake ɓuya a gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kafirai a lahira ba su da masu taimakon su da za su kare su daga azabar Allah duk kuwa da irin ƙarfi da tanadi da suke da shi a nan duniya.

2. Karfin da kafirai suke ganin suna da shi da irin shirin da suka yi a nan duniya, su ne suka jefa su cikin ruɗu da ɗimuwa.

3. Babban abin da yake ƙara wa kafirai kafirci shi ne girman kai da bijire wa gaskiya.

4. Mumini da kafiri ba za su taɓa zama daidai ba, duniya da lahira.

5. Duk ilimin kafiri da wayonsa a kife yake tafiya a rayuwarsa ta duniya, hakanan kuma zai kasance a rayuwar lahira.

6. Annabi (ﷺ) bawan Allah ne wanda Allah yake umartar sa ya kuma hana shi, domin shi mai isar da saƙo ne daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

7. Ji da gani da hankali ni’imomin Allah ne ga mutum da ya zama wajibi ya yi masa godiya a kansu.

8. Masu bin Allah da gode masa kaɗan ne daga cikin bayinsa, don haka zallar yawa ba ya zama hujja.

9. Tabbatar da zuwan ranar lahira, kuma ba wanda ya san lokacin zuwanta sai Allah kaɗai.

10. Azabar kafirai a lahira ta ƙunshi azabar gangar jiki da ta zuciya.

Suratul Mulk (20-27)

أَمَّنْ هَٰذَا ٱلَّذِى هُوَ جُندٌ لَّكُمْ يَنصُرُكُم مِّن دُونِ ٱلرَّحْمَٰنِ ۚ إِنِ ٱلْكَٰفِرُونَ إِلَّا فِى غُرُورٍ ﴿٢٠﴾ أَمَّنْ هَٰذَا ٱلَّذِى يَرْزُقُكُمْ إِنْ أَمْسَكَ رِزْقَهُۥ ۚ بَل
لَّجُّوا۟ فِى عُتُوٍّ وَنُفُورٍ ﴿٢١﴾ أَفَمَن يَمْشِى مُكِبًّا عَلَىٰ وَجْهِهِۦٓ أَهْدَىٰٓ أَمَّن يَمْشِى سَوِيًّا عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٢٢﴾ قُلْ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَكُمْ وَجَعَلَ لَكُمُ
ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَٱلْأَفْـِٔدَةَ ۖ قَلِيلًا مَّا تَشْكُرُونَ ﴿٢٣﴾ قُلْ هُوَ ٱلَّذِى ذَرَأَكُمْ فِى ٱلْأَرْضِ وَإِلَيْهِ تُحْشَرُونَ ﴿٢٤﴾ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلْوَعْدُ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ﴿٢٥﴾ قُلْ إِنَّمَا ٱلْعِلْمُ عِندَ ٱللَّهِ وَإِنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٌ مُّبِينٌ ﴿٢٦﴾ فَلَمَّا رَأَوْهُ زُلْفَةً سِيٓـَٔتْ وُجُوهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ وَقِيلَ هَٰذَا ٱلَّذِى كُنتُم بِهِۦ تَدَّعُونَ ﴿٢٧﴾

20. Ko kuwa wace runduna ce kuke da ita da za ta taimaka muku ba (Allah) Mai rahama ba? Su dai kafirai ba sa kan komai sai ruɗi.

21. Ko kuwa wane ne zai arzuta ku idan (Allah) Ya riƙe arzikinsa? A'a, kawai dai sun yi zurfi ne cikin taurin kai da fanɗarewa.

22. Shin wanda yake tafiya a kife a kan fuskarsa shi ya fi zama a kan daidai ko kuma wanda yake tafiya a miƙe kan hanya madaidaiciya?

23. Ka ce: "Shi ne (Allah) Wanda Ya fare ku Ya kuma sanya muku ji da gani da zukata; kaɗan ne kawai kuke godewa."

24. Ka ce: "Shi ne wanda Ya halicce ku a kan ƙasa, kuma zuwa gare Shi za a tattara ku."

25. Suna kuma cewa: "Yaushe ne wannan alƙawarin, idan kun kasance masu gaskiya?"

26. Ka ce: "Saninsa yana wurin Allah ƙawai, kuma ni kawai mai gargaɗi ne mai bayyana (gargaɗin)."

27. To lokacin da za su gan shi a kurkusa, sai fuskokin waɗanda suka kafirce suka yi baƙi, aka kuma ce: "Wannan ne abin da kuka kasance kuna neman zuwansa."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙalubalanci kafirai masu bautar wasu gumaka ba Allah ba da zaton za su amfanar da su da cewa, ba su da wata runduna wadda za ta kare su daga azabar Allah idan ya so yi musu azaba, don haka abin da suka runguma a matsayin abin bauta ba Allah ba, ba komai ba ne sai ruɗi irin na Shaiɗan wanda yake yaudarar su yana yi musu ingiza-mai-kantu-ruwa.
Ya kuma tabbatar musu cewa, babu wanda zai iya arzuta su idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya riƙe arzkinsa ya hana su, domin shi ne kaɗai mai arzutawa kuma mai hanawa, sai dai abin da yake faruwa shi ne kafirai sun doge a kan tsaurin kansu da girman kai da fanɗare wa gaskiya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da misalin mumini da kuma kafiri, inda ya bayyana cewa, ba za a taba daidaita mushiriki mai bautar wasu gumaka ba Allah ba, yake tafiya a kife a kan fuskarsa ba shi da wata takamaimiyar alƙibla, a haɗa shi da mumini mai kaɗaita Allah wanda yake tafiya a miƙe kyam a kan tafarki madaidaici. Watau duba ga waɗannan mutane biyu kaɗai zai sa a gane babban bambancin da ke tsakaninsu ba tare da an sha wata wahala ba. Hakanan a lahira za a tashi mumini yana tafiya a miƙe kyam a kan miƙaƙken tafarki wanda zai kai shi har Aljanna, shi kuma kafiri za a tashe shi yana tafiya a kife a kan fuskarsa bai san inda ya dosa ba har zuwa wutar Jahannama.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Za a tashi mutane a ranar alƙiyama kashi uku; akwai masu tafiya da ƙafafunsu; akwai kuma mahaya ababen hawa; akwai masu tafiya a kan fuskokinsu. Sai sahabbai suka ce: "Ya Manzon Allah, yaya za su riƙa tafiya a kan fuskokinsu?" Sai ya ce: "Wanda ya ba

su damar su riƙa tafiya a kan ƙafafunsu shi ne mai ikon ya tafiyar da su a kan fuskokinsu, kuma lalle za su yi ta kauce wa ƙaya da rami da fuskokinsu.” [Ahmad #8647 da Tirmizi #3141].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya shaida wa mushirikai masu ƙaryata shi cewa lalle Allah shi ne wanda ya halicce su ya ba su kunnuwan da suke ji da su, ya kuma ba su idanu da suke gani da su, ya ba su zukata waɗanda suke fahimta da su. Allah ya yi musu waɗannan ni’imomi ne don su gode masa su bauta masa shi kaɗai, amma sai ga shi kaɗan ne daga cikinsu suke gode masa.
Sai kuma Allah ya kuma bayyana musu cewa, shi ne wanda ya halicce su ya kuma baza su a bayan ƙasa, gumakansu kuma ba sa iya halittar komai, don haka su sani cewa zuwa ga Allah ne kaɗai za a tattara su a ranar alƙiyama domin yi musu hisabi da sakamako, gumakansu kuwa ba su da wannan ikon, saboda haka su ji tsoron Allah su bauta masa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da wani abokin tarayya ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin taurin kan mushirikai, domin duk wannan wa’azi da jan hankali da yake yi musu sai ga shi suna tambayar Annabi (ﷺ) da sahabbansa cewa, su faɗa musu yaushe ne alƙawarin tashin alƙiyama zai zo, in har da gaskiya ne alƙiyamar za ta zo?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya mayar musu da martani da cewa, sanin zuwan ranar alƙiyama yana ga Allah shi kaɗai, babu wani da ya san sanda za ta zo sai shi, shi kansa Manzon Allah (ﷺ) bai sani ba, domin shi kawai mai bayyana gargaɗi ne a gare su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yayin da kafirai za su ga abin da ake yi musu alƙawarinsa na azaba ya zo dab da su, a ranar alƙiyama, to a nan ne fuskokinsu za su canja su yi baƙi ƙirin saboda ɓacin rai da tashin hankali, su kuma mala’iku su yi ta faɗa musu cewa, wannan shi ne abin da suke nema tun a duniya, da a gaggauto musu da shi, to ga shi ya zo kusa da su.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin gabar mushirikai ga Manzon Allah (ﷺ) wanda har ta kai su ga burin ganin mutuwarsa tare da waɗanda suka yi imani da shi.

2. Mutuwar mai wa’azi ko rayuwarsa ba su ne za su kare kafirai daga azabar Allah ba idan ta zo musu.

3. Ga Allah kaɗai ya wajaba muminai su dogara, domin shi ne mai kare su daga sharrin duk wani mai sharri.

4. Mafi girman ni’ima ta duniya ita ce ruwa wanda a hannun Allah yake, shi ne kaɗai mai saukar da shi da gudanar da shi a bayan ƙasa domin amfanin halittunsa, idan har ya riƙe kayansa, to babu wani mahaluƙi da zai iya dawo da shi. Don haka wajibi ne ga bayi su koma ga Allah wanda mulkin komai yake a hannunsa, su bauta masa shi kaɗai don su ci ribar rayuwarsu kafin mutuwarsu.

Suratul Mulk (28-30)
قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِنۡ أَهۡلَكَنِيَ ٱللَّهُ وَمَن مَّعِيَ أَوۡ رَحِمَنَا فَمَن يُجِيرُ ٱلۡكَٰفِرِينَ مِنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ ٢٨ قُلۡ هُوَ ٱلرَّحۡمَٰنُ ءَامَنَّا بِهِۦ وَعَلَيۡهِ تَوَكَّلۡنَاۖ فَسَتَعۡلَمُونَ مَنۡ هُوَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٢٩ قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِنۡ أَصۡبَحَ مَآؤُكُمۡ غَوۡرٗا فَمَن يَأۡتِيكُم بِمَآءٖ مَّعِينِۢ ٣٠

28. Ka ce: “Ku ba ni labari, idan Allah Ya hallaka ni da waɗanda suke tare da ni, ko kuma Ya ji ƙan mu, to wane ne zai kare kafirai daga azaba mai raɗaɗi?”

29. Ka ce: “Shi ne (Allah) Mai rahama, mun yi imani da Shi, kuma a gare Shi muka dogara, to da sannu za ku san shin wane ne yake cikin ɓata mabayyani?”

30. Ka ce: “Ku ba ni labari, idan ruwanku ya wayi gari a ƙafe, to wane ne zai zo muku da ruwa mai ɓuɓɓugowa?”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya mayar da martani ga kafirai masu fatan ganin mutuwarsa da abubuwa biyu:

Na farko, ya nemi su faɗa masa cewa idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karɓi ransa shi da muminai da suke tare da shi ko ya ji ƙan su ya jinkirta musu, to wane amfani za su samu a cikin wannan? Wane ne su kuma zai kuɓutar da su daga azabar Allah mai raɗaɗi idan ta zo musu? Suna tsammanin gumakansu za su amfane su ne? Ko kaɗan babu abin da zai musu amfani idan ba imani da Allah shi kaɗai ba.

Na biyu, ya sanar da su cewa, Allah shi ne mai rahama wanda yake kiran su zuwa ga bauta masa shi kaɗai, shi kuma ya yi imani da shi a matsayin abin bauta guda ɗaya, kuma gare shi kaɗai, shi da mabiyansa muminai, suke dogara cikin dukkan al’amuransu, don haka shi ne mai tsare su daga azabar lahira, kuma tabbas ba da jimawa ba za su sani wanda yake cikin ɓata mabayyani ko wanda yake kan tafarki madaidaici, su ne ko shi?
Sannan a ayar ƙarshe ta wannan Sura, Allah ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya nemi kafirai su ba shi labari idan aka wayi gari ruwan shansu ya ƙafe ƙaƙaf, to wane ne zai kawo musu wani ruwa mai ɓuɓɓuga a madadinsa, wanda za su riƙa sha suna shuka suna shayar da dabbobinsu? Tabbas babu mai iya yi musu wannan sai Allah shi kaɗai, to me ya hana su dogara gare shi shi kaɗai, su bauta masa ba tare da haɗa shi da abokin tarayya ba?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ishara zuwa ga mu’ujizar Alƙur’ani mai girma.

2. Fito da darajar ilimi da hanyoyin neman sa da ni’imar koyar da ɗan’adam rubutu wanda da shi ne ake kare addini, ake kuma kiyaye ilimi, kuma rubutu hanya ce ta fahimtar juna tsakanin 'yan’adam.

3. Tabbatar da girman matsayin Annabi (ﷺ) da wanke shi daga duk wata tuhuma da mushirikai suke yi masa, kamar tuhumar sa da hauka.

4. Babbar ni’ima da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa Muhammadu (ﷺ) ta annabci da wahayi.

5. Ladan Annabi (ﷺ) ba zai yanke ba har abada, saboda shiriya da ya zo wa mutum da aljan da ita.

6. Yabon Manzon Allah (ﷺ) da halaye manya-manya waɗanda ya koye su daga Alƙur’ani mai girma.

7. Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da nuna masa cewa, shi ne zai yi galaba a kan kafirai ba da jimawa ba.

68-Suratul Kalam

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Ana kiran ta '*Suratul Kalam*' saboda kalmar '*Al-Kalam*' da ta zo a ayar farko. A wasu littattafan tafsiri da dama haɗe da littafin *Sahihul Bukhari* an kira ta da '*Suratu Nun Wal Kalam*'.
Imamut Tirmizi da wasu malaman tafsiri kuwa sun kira ta da '*Suratu Nun*'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* ba tare da wani saɓani ba, kamar yadda Ibn Aɗiyya ya ambata.

3. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta hamsin da biyu ne (52) ba tare da wani saɓani ba.

4. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta uku (3) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Muddassir*'.

5. Babban Jigonta:
Goyon bayan Manzon Allah (ﷺ) da bayyana kyawawan ɗabi'unsa bayan mushirikai sun nuna masa rashin kunya da tsangwama.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Ishara zuwa ga mu'ujizar Alƙur'ani da kasancewarsa littafi ne gagara-koyo.
• Fito da muhimmancin rubutu da kayan rubutu da kuma su kansu marubuta, da nuni zuwa ga mu'ujizar Manzon Allah (ﷺ) na zamantowarsa wanda ya fi kowa ilimi tare da cewa shi ummiyyi ne, watau ba ya rubutu ba ya karanta abin da aka rubuta.
• Rushe soke-soken mushirikai ga Manzon Allah (ﷺ).
• Tabbatar da cikar kamalarsa a duniya da lahira da girman shiriyarsa da taɓewar waɗanda suka saɓa masa suka ƙaryata shi.
• Sukan shugabannin mushirikai da bayanin miyagun halayensu da yi musu narkon azaba a duniya da lahira, tare da ba su misali na wasu al'ummu da suka butulce wa ni'imar Allah, ya saukar musu da azabarsa tun a nan duniya.
• Falalar muminai waɗanda Allah ya zaɓe su ya yi musu baiwa da ni'imar Musulunci. Su kuma kafirai gumakansu ba za su amfane su da komai ba a duniya da lahira.
• Yi wa mushirikai wa'azi da nuna musu cewa, ni'imar da suke rayuwa a cikinta talala ce kawai daga Allah, yana kuma yi musu haka ne saboda makircin da suke shirya wa Musulmi, don haka ba su da sauran wani hanzari game da rashin karɓa kiran Manzon Allah (ﷺ) saboda ɗagawarsu da taurin kansu.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) a kan ya yi haƙuri game da cutarwar mutanensa a gare shi saboda ya kira su zuwa gaskiya, kada kuma ya nuna ƙosawa game da isar da saƙon Allah kamar yadda Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi har Allah ya zarge shi a kan haka.

Suratul Kalam (1-7)

نٓ وَٱلۡقَلَمِ وَمَا يَسۡطُرُونَ ١ مَآ أَنتَ بِنِعۡمَةِ رَبِّكَ بِمَجۡنُونٖ ٢ وَإِنَّ لَكَ لَأَجۡرًا غَيۡرَ مَمۡنُونٖ ٣ وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٖ ٤ فَسَتُبۡصِرُ وَيُبۡصِرُونَ ٥ بِأَيِّيكُمُ ٱلۡمَفۡتُونُ ٦ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعۡلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِٱلۡمُهۡتَدِينَ ٧

Da sunan Allah, Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. NUN. (Allah ya ce): Na rantse da alƙalami da abin da (mala'iku) suke rubutawa.

2. Kai ba mahaukaci ba ne saboda ni'imar Ubangijinka.

3. Kuma lalle tabbas kana da lada marar yankewa.

4. Lalle kuma kai kana kan halaye masu girma.

5. To ba da daɗewa ba za ka gani, su ma kuma su gani.

6. Wane ne daga cikinku mahaukaci?

7. Lalle Ubangijinka Shi Ya fi sanin wanda ya kauce wa hanyarsa kuma Shi Ya fi sanin shiryayyu.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da harafin '*Nun*' kamar yadda ya buɗe wasu surori da irin waɗannan haruffa don nuna mu'ujizar Alƙur'ani da zamantowarsa gagara-koyo duk kuwa da kasancewarsa yana magana ne da irin haruffan da su kansu Larabawa gwanayen fasaha suke magana da su. [Dubi farkon tafsirinmu na *Suratul Baƙara* don ƙarin bayani].
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rantse da Alƙalami da abin da mutane suke rubutawa da alƙalumansu na littattafai a fannonin ilimi daban-daban. Mafificin alƙalami shi ne wanda aka rubuta ayyukan bayi da shi a *Lauhul Mahfuzu*.

An karɓo daga Ibn Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle farkon abin da Allah ya halitta shi ne Alƙalami, ya kuma umarce shi ya rubuta komai." [Abu Ya'ala #2329].

An karɓo daga Ubadatu ɗan Samit (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lalle farkon abin da Allah ya halitta shi ne Alƙalami sai ya ce masa: "Yi rubutu." Sai ya ce: "Ya Ubangijina, me zan rubuta?" Sai ya ce: "Ka rubuta abubuwan da aka ƙaddara na komai har zuwa tashin alƙiyama." [Abu Dawud #4700 da Tirmizi #2155].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, saboda ni'imar annabci da ya yi wa Manzonsa (ﷺ) ba zai taɓa zama mahaukaci ba, don haka ba shi da alaƙa da tuhumar da mushirikai suke yi masa ta cewa wai shi mahaukaci ne don ya zo musu da Alƙur'ani.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, Annabi (ﷺ) yana da lada marar yankewa a kan wahalhalun da yake sha wajen isar wa mutane saƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma babu wani mahluƙi da zai goranta wa Manzo (ﷺ) a kan haka. Sai kuma ya yi masa kyakkyawar shaida da cewa yana kan halaye masu girma, domin yana koyi ne da kyawawan halayen da Alƙur'ani ya zo da su.

An karɓo daga Sa’ad ɗan Hisham ɗan Amir ya ce: Na zo wurin A’isha, (Allah ya kara mata yarda), na ce: “Ya Ummal Muminina, ba ni labarin halayen Manzon Allah (ﷺ).” Sai ta ce: “Halayensa sun kasance Alƙur’ani ne. Shin ba ka karanta Alƙur’ani ne? Ba ka ga faɗar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba inda ya ce: “Lalle kai kana kan halaye masu girma”?” [Ahmad #24601].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya razana mushirikai da cewa ba da jimawa ba Annabi (ﷺ) zai gani, su ma kuma masu ƙaryata shi za su gani cewa a tsakaninsa da su, wane ne mahaukaci lokacin da gaskiya za ta bayyana ga kowa?
Ya kuma tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, Ubangijinsa yana sane da wanda ya ɓace daga kan hanyarsa, yana kuma sane da shiryayyu masu bin hanyar Allah. Watau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san su ne ɓatattu waɗanda suka kauce wa hanyarsa, ya kuma san cewa Annabi (ﷺ) shi ne shiryayye da yake kan hanyar gaskiya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi (ﷺ) bawan Allah ne, Allah yana umartar sa, yana kuma hana shi.

2. Hana yi wa kafirai biyayya game da guje wa kira zuwa ga kaɗaita Allah da kyawawan halaye.

3. Kafirai suna fatar ina ma da Musulmi za su daina kira zuwa ga Musulunci, don a samu kusantar juna da haɗin kai a tsakanin mabambanta addinai, don haka Allah ya yi kira da a ƙaurace wa wannan mummunar manufar tasu don buƙatarsu ita ce rushe addinin gaskiya da dakatar da yaɗuwarsa a cikin al’ummunsu.

4. Hani a kan yawan rantsuwa musamman ga wanda ya san ƙarya yake, domin yin haka shi ya fi matuƙar muni.

5. Haramcin zunɗe da yi da mutane da gulma, domin duk waɗannan siffofin kafirai ne masu ƙaryata gaskiya.

6. Haramcin rowa ga wanda Allah ya ba shi dukiya da hana wasu aikata alheri.

7. Haramcin ƙetare iyakokin Allah da aikata ta’addanci ga mutane.

8. Daga cikin miyagun halaye akwai kaushin zuciya da girman kai da ƙin gaskiya.

9. Munin ɗabi’ar ruɗuwa da yawan dukiya ko yawan ‘ya’ya, domin hakan yakan sa waɗansu girman kai da ƙin gaskiya.

10. Duk wanda ya haɗa waɗannan miyagun siffofi da suka zo a waɗannan ayoyin lalle yana daga cikin mafi sharrin mutane.

11. Waɗannan miyagun ɗabi’u da aka jero a waɗannan ayoyi biyu, babu wata ingantacciyar ruwaya da take fayyace sunan mutumin da ake nufi a nan, duk kuwa da cewa wasu malaman tafsiri sun ambato sunayen wasu kafirai da dama suna danganta su da waɗannan ɗabi’u. Amma kuma waɗannan siffofi sun yi kama da waɗanda aka kawo a *Suratul Muddassir,* aya ta 11 zuwa ta 26. Hadisi kuwa ya inganta daga Abdullahi ɗan Abbas cewa, ayoyin *Suratul Muddassir* sun sauka ne a kan Al-Walidu ɗan Mugira. [Dubi, Al-Hakim, *Al-Mustadrak* #3872].

Suratul Kalam (8-16)

فَلَا تُطِعِ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ۝٨ وَدُّواْ لَوۡ تُدۡهِنُ فَيُدۡهِنُونَ ۝٩ وَلَا تُطِعۡ كُلَّ حَلَّافٖ مَّهِينٍ ۝١٠ هَمَّازٖ مَّشَّآءِۭ بِنَمِيمٖ ۝١١ مَّنَّاعٖ لِّلۡخَيۡرِ مُعۡتَدٍ أَثِيمٍ ۝١٢ عُتُلِّۭ بَعۡدَ ذَٰلِكَ زَنِيمٍ ۝١٣ أَن كَانَ ذَا مَالٖ وَبَنِينَ ۝١٤ إِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِ ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ۝١٥ سَنَسِمُهُۥ عَلَى ٱلۡخُرۡطُومِ ۝١٦

8. Saboda haka kada ka bi masu ƙaryatawa.

9. Sun yi burin da za ka sassauto, sai su ma su sassauto.

10. Kada kuma ka bi duk wani mai yawan rantsuwa, wulaƙantacce.

11. Mai yawan yin zunɗe, mai yawan yawo da annamimanci.

12. Mai yawan hana alheri, mai ta’addanci, mai yawan sabo.

13. Mai busasshiyar zuciya, bayan wannan kuma marar asali ne.

14. Don ya kasance mai dukiya da ‘ya’ya.

15. Idan ana karanta masa ayoyinmu sai ya ce: “Tatsuniyoyin mutanen farko ne.”

16. Ba da daɗewa ba za Mu yi masa alama a kan hancinsa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana daɗa ƙarfafa gwiwar Manzonsa (ﷺ) a kan kira da yake yi wa kafirai zuwa ga gaskiya, ya kuma gargaɗe shi da cewa kada ya biye wa masu ƙaryata Alƙur’anin da ya zo da shi. Har ma koyaushe buri suke yi ina ma Manzon Allah (ﷺ) zai yi musu wata kara ya sassauta musu wajen aibata gumakansu da allolinsu, sai su ma su yi masa kara su sassauto su daina sukan sa da sukan addininsa.

Sannan Allah ya yi wa Manzonsa kashedi da kada ya kuskura ya yi biyayya ga duk wani kafiri mai yawan rantsuwa a kan ƙarya, wulaƙantacce marar mutunci, mai yawan zunɗe da yi da mutane a bayan idonsu, mai yawan yawo da yaɗa annamimanci don ɓata tsakanin mutane da raba kawunansu, mai yawan hana gudanar alheri; shi ba zai yi ba kuma ba zai ƙyale masu yi su yi ba, mai yawan ta’addanci a kan dukiyoyin mutane da mutuncinsu da rayukansu, ya hana kowa sakat da walwala, mai yawan aikata zunubai da laifuka, babu tsoron Allah a zuciyarsa, mai ƙeƙasasshiyar zuciya da kakkausan hali wajen mu’amala da mutane; babu tausayi a ransa, ga shi kuma marar asali a cikin mutanensa, mugu, mai nuna girman kai da ƙin gaskiya don kawai ya ga yana da tarin dukiya da ‘ya’ya, har wannan ya sanya shi idan an karanta masa ayoyin Allah ana yi masa wa’azi da gargaɗi sai ya buɗi baki ya ce, ai duk wannan tatsuniyoyin mutanen farko ne, don haka shi ba zai yi imani ba.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa kashedi da azabarsa da cewa, ba da jimawa ba zai tagayyara shi ta hanyar yi masa alama a karan hancinsa da za ta munana shi muni na har abada.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ruɗuwa da yalwar arziki wadda za ta kai mutane zuwa ga watsi da gaskiya da raina masu kira zuwa ga addini da rashin godiya ga Allah wanda ya ni'imta su da wannan ni'ima, shi ne abin da ya jawo wa al'ummun da suka gabata azabar Allah da narkonsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jarrabi mutanen Makka da ni'imomi daban-daban, kamar ni'imar zaman lafiya da kwanciyar hankali da hore musu hanyoyin kasuwanci zuwa garuruwa daban-daban, sannan ya cika musu da wata babbar ni'ima ta aiko aiko musu da Manzon Allah (ﷺ) wanda ya zo musu da shiriya da addinin gaskiya, amma kuma sai suka nuna ɗagawa da butulci ga Allah, ba su dubi ɗimbin ni'imomin da ya yi musu ba, sun gode masa, sun karɓi kiran Manzonsa.

3. Samun albarkar amfanin gona babbar ni'ima ce daga ni'imomin Allah, don haka dole ne bayi su yi masa godiya a kan haka, su fitar da haƙƙin mabuƙata a cikinta su guji rowa domin tana da mummunan ƙarshe.

4. Wajabcin faɗar 'insha Allah' yayin da mutum ya ƙudurci aikata wani aiki, domin rashin hakan yakan jawo mummunar asara.

5. Uƙubar Allah takan auko wa mai laifi ba zato ba tsammani, yana tsaka da barci ko yana cikin hada-hadarsa da rafkanarsa.

6. Kulla ƙaƙƙarfar niyya a kan aikata wani aiki mai kyau ko mummuna yana matsayin zartar da shi ko da mutum bai sami damar aikatawa ba, matuƙar ba tsoron Allah ne ya hana shi aikatawa ba.

7. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nufi bawansa mai laifi da alheri sai ya gaggauto masa da wata uƙubar laifinsa tun a nan duniya, wadda za ta sa shi ya tuba ya koma ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

8. Tasbihi da ambaton Allah sukan kare bawa daga aukawa cikin saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ko dogewa a kansa.

9. Azabar lahira ta fi azabar duniya tsanani da girma.

10. Ba dole ne duk wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa wata uƙuba a nan duniya sai ya yi masa ita a lahira ba, za a iya yi masa uƙuba a nan duniya a yafe masa ta lahira; hakanan za a iya yi masa uƙuba a lahira ko da ba a yi masa ta duniya ba ; za kuma a iya haɗa masa duka biyun

Suratul Kalam (17-33)

إِنَّا بَلَوۡنَٰهُمۡ كَمَا بَلَوۡنَآ أَصۡحَٰبَ ٱلۡجَنَّةِ إِذۡ أَقۡسَمُواْ لَيَصۡرِمُنَّهَا مُصۡبِحِينَ ١٧ وَلَا يَسۡتَثۡنُونَ ١٨ فَطَافَ عَلَيۡهَا طَآئِفٞ مِّن رَّبِّكَ وَهُمۡ نَآئِمُونَ ١٩
فَأَصۡبَحَتۡ كَٱلصَّرِيمِ ٢٠ فَتَنَادَوۡاْ مُصۡبِحِينَ ٢١ أَنِ ٱغۡدُواْ عَلَىٰ حَرۡثِكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰرِمِينَ ٢٢ فَٱنطَلَقُواْ وَهُمۡ يَتَخَٰفَتُونَ ٢٣ أَن لَّا يَدۡخُلَنَّهَا
ٱلۡيَوۡمَ عَلَيۡكُم مِّسۡكِينٌ ٢٤ وَغَدَوۡاْ عَلَىٰ حَرۡدٖ قَٰدِرِينَ ٢٥ فَلَمَّا رَأَوۡهَا قَالُوٓاْ إِنَّا لَضَآلُّونَ ٢٦ بَلۡ نَحۡنُ مَحۡرُومُونَ ٢٧ قَالَ أَوۡسَطُهُمۡ أَلَمۡ أَقُل لَّكُمۡ
لَوۡلَا تُسَبِّحُونَ ٢٨ قَالُواْ سُبۡحَٰنَ رَبِّنَآ إِنَّا كُنَّا ظَٰلِمِينَ ٢٩ فَأَقۡبَلَ بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖ يَتَلَٰوَمُونَ ٣٠ قَالُواْ يَٰوَيۡلَنَآ إِنَّا كُنَّا طَٰغِينَ ٣١ عَسَىٰ رَبُّنَآ أَن
يُبۡدِلَنَا خَيۡرٗا مِّنۡهَآ إِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا رَٰغِبُونَ ٣٢ كَذَٰلِكَ ٱلۡعَذَابُۖ وَلَعَذَابُ ٱلۡأٓخِرَةِ أَكۡبَرُۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٣٣

17. Lalle Mu Mun jarrabe su (wato mutanen Makka) kamar yadda Muka jarrabi ma'abota gona, lokacin da suka rantse cewa, lalle tabbas za su girbe ta da asussuba.

18. Ba sa kuma togaciya (da faɗar *insha Allah*).

19. Sai wani bala'i daga Ubangijinka ya kewaye ta alhali su suna bacci.

20. Sai ta wayi gari (baƙi ƙirin) kamar duhun dare.

21. Sai suka kirawo junansu da asussuba.

22. Cewa: "Ku yi sammako ga amfanin gonarku idan kun kasance masu yin girbi."

23. Sai suka tafi alhali suna yi wa junansu raɗa.

24. Cewa: "Lalle a yau kada wani miskini ya shigar muku cikinta."

25. Suka kuwa yi sammako suna masu zaton su masu iko ne a kan hana (mabuƙata).

26. To lokacin da suka gan ta sai suka ce: "Lalle mu tabbas mun yi ɓatan kai.

27. "A'a, mu dai an hana mu ne kawai."

28. Sai wanda ya fi su kirki ya ce: "Ban gaya muku ya kamata ku tsarkake Allah ba?"

29. Suka ce, "Tsarki ya tabbata ga Ubangijinmu, lalle mu mun kasance azzalumai."

30. Sai sashinsu ya fuskanci sashi suna zargin juna.

31. Suka ce: "Kaiconmu, lalle mu mun kasance masu shisshigi.

32. "Tsammanin Ubangijinmu zai musanya mana wadda ta fi ta, lalle mu masu kwaɗayi ne a wurin Ubangijinmu."

33. Kamar haka ne azaba take tabbata; kuma tabbas azabar lahira ta fi girma. Da sun kasance sun san haka.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi bayanin cewa, duk wanda ya hore masa dukiya, to ya ba shi ita ne don ya jarrabe shi ya ga ko zai gode masa, zai kuma sarrafa ta wajen bin Allah da taimakon mabuƙata, ko kuma zai butulce masa ne, ya yi rowa da wadatar da ya ba shi, Allah kuma ya ƙwace dukiyar ya raba shi da ita.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, ya jarrabi mutanen Makka da fari da yunwa, kamar yadda ya jarrabi wasu mutane masu gona, lokacin da suka ga ta nuna ta isa girbi sai suka yi rantsuwa cewa, lalle da sassafe za su fita da gaggawa su je su girbe amfanin gonarsu, don kada wani mabuƙaci ya sami labari ya zo ya roƙe su taimakon abinci, amma suka ƙi cewa 'insha Allahu' a lokacin rantsuwarsu, ba su san Allah yana nan a madakata ba, sai kuwa ga shi ya aiko musu wata wuta da ta cinye amfanin gonar nan tatas, a lokacin da suke can suna sharar barci ba su san me yake faruwa ba. Don haka babu yadda za su iya kare ta daga wannan bala'in gobara. Gona ta ƙone ƙurmus ta wayi gari baƙa ƙirin kamar duhun dare.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan masu gona da muku-mukun asuba suka riƙa kiran junansu, da cewa, lalle su yi sammako su fita zuwa gonarsu kafin mabuƙata su farka su san abin da suke ciki, suka ƙarfafa wa juna cewa, lalle su hanzarta idan har suna son girbe amfanin gonarsu ba tare da

wani ya amfana da shi ba. Suka daka sammako suka kama hanya cikin gaggawa suna yi wa junansu raɗa cewa, kada su bari wani miskini ya shigar musu gonarsu, suna zaton cewa za su iya hana mabuƙata amfanin gonarsu. Suna isa sai suka ga gonarsu ta ƙone ƙurmus, sai wasunsu suka ce, haƙiƙa sun yi ɓatan kai, domin wannan ba ita ce gonarsu ba, sai wasu kuma suka tabbatar da cewa, ba ɓatan kai suka yi ba, sun ɗai tabka asara ne, saboda mummunan ƙudurinsu na hana mabuƙata haƙƙinsu. Sai wanda ya fi su kirki ya tuna musu da abin da ya faɗa musu lokacin da suke tattaunawa a kan za su hana mabuƙata haƙƙoƙinsu, inda ya faɗa musu cewa, me ya hana su su riƙa tsarkake Allah suna masa tasbihi, su tuba su koma gare shi? Amma kuma suka ƙi jin nasiharsa, sai bayan wannan mummunar musiba ta auka musu sannan ne za su koma suna cewa tsarki ya tabbata ga Ubangijinsu. Ba shakka sun tabbata azzalumai waɗanda suka cuci kansu yayin da suka yi niyyar hana mabuƙata haƙƙinsu daga amfanin gonarsu. Daga nan nadama ta lulluɓe su suka fuskanci junansu suna zargin kansu, sai suka sake tabbatar wa da juna cewa kaiconsu, lalle sun kasance masu ƙetare iyakar Ubangijinsu yayin da suka ɗauka cewa, za su iya cinye haƙƙin talakawa su kwana lafiya. A nan ne kuma suka dawo cikin nadama suna roƙon Allah, tare da fatan ya canja musu da wata gonar wadda ta fi tasu, domin yanzu kam sun koma gare shi shi kaɗai suna kwaɗayin ya ba su wata gonar da ta fi tasu, suna kuma fatan ya yi musu afuwa, ya yafe musu kuskuren da suka tafka har ya kai su ga wannan mummunan yanayi da suke ciki.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da irin wannan azabar ne yake hana arzikinsa ga wasu masu saɓon sa, zai kuma azabtar da duk wanda zai butulce masa, ya zabi saba masa, a duniya zai ga azaba irin wannan. Ya kuma kamata su sani cewa, azabar lahira ta fi wannan girma nesa ba kusa ba. Da a ce su mutane ne masu hankali da basira da sun wa'azantu, sun guji saba wa Allah sun dawo cikin hayyacinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Masu taƙawa su ne masu samun shiga gidan Aljanna.

2. Mumini da kafiri ba za su daidaita a wajen sakamako ba, kamar yadda ba ɗaya suke a siffofinsu da ayyukansu ba.

3. Martani ga mushirikai masu da'awar cewa, ko a lahira suna da sakamako kamar na muminai ko ma fiye da su.

4. Daidaita tsakanin Musulmi da kafiri, wani hukunci ne na zalunci a wurin Allah.

Suratul Kalam (34-41)
إِنَّ لِلۡمُتَّقِينَ عِندَ رَبِّهِمۡ جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ٣٤ أَفَنَجۡعَلُ ٱلۡمُسۡلِمِينَ كَٱلۡمُجۡرِمِينَ ٣٥ مَا لَكُمۡ كَيۡفَ تَحۡكُمُونَ ٣٦ أَمۡ لَكُمۡ كِتَٰبٞ فِيهِ تَدۡرُسُونَ ٣٧
إِنَّ لَكُمۡ فِيهِ لَمَا تَخَيَّرُونَ ٣٨ أَمۡ لَكُمۡ أَيۡمَٰنٌ عَلَيۡنَا بَٰلِغَةٌ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ إِنَّ لَكُمۡ لَمَا تَحۡكُمُونَ ٣٩ سَلۡهُمۡ أَيُّهُم بِذَٰلِكَ زَعِيمٌ ٤٠ أَمۡ لَهُمۡ
شُرَكَآءُ فَلۡيَأۡتُواْ بِشُرَكَآئِهِمۡ إِن كَانُواْ صَٰدِقِينَ ٤١

34. Lalle masu taƙawa suna da gidajen Aljannar ni'ima a wurin Ubangijinsu.

35. Yanzu za Mu sanya Musulmi kamar kangararru?

36. Me ya same ku ne, yaya kuke irin wannan hukuncin?

37. Ko kuna da wani littafi ne wanda a cikinsa kuke karantawa?

38. (Cewa) a cikinsa lalle kuna da abin da kuke zaɓa?

39. Ko kuwa kuna da wasu alƙawura na rantsuwa ne (tabbatattu) a kanmu har zuwa ranar alƙiyama cewa, lalle kuna da abin da kuke hukunta wa (kanku)?

40. Ka tambaye su wane ne a cikinsu ya yi lamuni game da wannan?

41. Ko kuwa suna da wasu ababan tarayya ne? To su kawo ababan tarayyar tasu idan sun kasance masu gaskiya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ni'imar da ya tanadar wa muminai masu kiyaye dokokinsa, suna aikata abin da ya umarce su, suna kuma guje wa haninsa, Allah ya yi musu tanadin gidajen Aljanna na ni'ima waɗanda za su shige su, su mori ni'imomin cikinsu ba tare da yankewa ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a bisa girman hikimarsa ba zai taɓa daidaita tsakanin Musulmi masu bin dokokinsa da kafirai kangararru ba, kamar yadda mushirikan Makka suke da'awar cewa, su ma a lahira za a ba su fiye da abin da za a ba wa muminai na jin daɗi, in har da gaske ne akwai ranar lahira ɗin. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaryata wannan da'awa tasu da cika baki na banza da wofi, ya soke su da kakkausar murya cewa, me ya same su ne suke faɗar irin wannan ɗanyen hukunci mai cike da zalunci? Ko suna da wani littafi ne wanda a cikinsa suka karanta daidaito tsakanin mai bin Allah da mai saɓa masa, suka kuma sami cewa lalle su a lahira suna da abin da suke zaɓa wa kansu? Idan kuwa ba haka ba, to shin suna da wasu tabbatattun alƙawura na rantsuwa ne da suka yi da Allah cewa lalle suna da abin da suke hukunta wa kawunansu na sakamako?
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nemi Manzonsa (ﷺ) ya tambaye su, wane ne a cikinsu ya lamunce musu wannan sakamako da suka zaɓa wa kawunansu ? Idan duk ba haka ba, to suna da wasu ababan tarayya da Allah ne waɗanda su ne za su daidaita sakamakonsu da na muminai a lahira? To idan sun ce suna da su to sai su kawo su idan sun kasance masu gaskiya, su zo su yi musu abin da suke da'awa. Tabbas sun san ƙarya suke ba su da wannan.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da abubuwa masu tsananin ban tsoro a ranar alƙiyama, bisa tafsirin malaman da suka fassara 'yaye ƙwauri' da cewa ana nufin tsananin tsoro.

2. Tabbatar wa Allah ƙwauri kamar yadda ya dace da girmansa, a kan ƙaulin waɗanda suka fassara ayar da hadisin Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya kara masa yarda).

3. Irin aikin mutum a nan duniya shi ne irin sakamakonsa a ranar lahira, kamar yadda kafirai da munafukai suka ƙi yin sujjada a duniya don Allah, to hakanan zai hana musu damar yin sujjada a lahira domin ya kunyata su.

4. Kasƙancin da kafirai za su fuskanta a lahira saboda taurin kansu da bijire wa gaskiya.

Suratul Kalam (42-43)
يَوۡمَ يُكۡشَفُ عَن سَاقٖ وَيُدۡعَوۡنَ إِلَى ٱلسُّجُودِ فَلَا يَسۡتَطِيعُونَ ٤٢ خَٰشِعَةً أَبۡصَٰرُهُمۡ تَرۡهَقُهُمۡ ذِلَّةٞۖ وَقَدۡ كَانُواْ يُدۡعَوۡنَ إِلَى ٱلسُّجُودِ وَهُمۡ سَٰلِمُونَ ٤٣

42. (Ka tuna) ranar da za a yaye ƙwauri a kuma kirawo su zuwa yin sujjada sannan su rasa ikon yi.

43. Idanuwansu a ƙasƙance, wulaƙanci ya lulluɓe su. Haƙiƙa kuwa a duniya sun kasance ana kiran su zuwa yin sujjada alhali suna lafiyayyu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana tsananin azaba da mawuyacin hali da kafirai za su fuskanta a ranar alƙiyama domin a ranar ne abubuwan ban tsoro masu girma za su bayyana, a lokacin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai zo don yin hukunci tsakanin bayinsa, sai ya kware ƙwaurinsa mai daraja wanda bai yi kama da wani abu na halittarsa ba, lokacin ne bayinsa za su ƙara sanin girmansa da darajarsa, sai a kirawo su zuwa ga yin sujjada, sai muminai su faɗi su yi masa sujjada, kafirai da munafukai kuwa su yi tsaye ƙiƙam su ƙasa yin sujjada, idanuwansu a ƙasƙance, nadama da wulaƙanci sun lulluɓe su, alhali sun kasance a duniya an neme su da su yi wa Allah sujjada lokacin da suke cikin ƙoshin lafiya, amma suka ƙi yi, don haka a ranar alƙiyama Allah zai fallasa su, ya bayyana ainihin taurin kansu da mummunan halinsu.

An karɓo daga Abu Sa’id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: Ubangijinmu zai yaye Kwaurinsa, sai kowane mumini namiji da kowace mumina mace su yi masa sujjada, sai wanda a duniya yake yi masa sujjada don riya ko don a faɗa, ya yi saura (a tsaye), sai ya yunƙura zai yi sujjada sai gadon bayansa ya koma falle ɗaya, (watau ya sandare).” [Bukhari #4919 da Muslim #183].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoratar da kafirai masu ƙaryata Alƙur’ani da lallashin Manzon Allah (ﷺ), tare da yi masa alƙawarin samun nasara a kan maƙiyansa.

2. Tambayar mutane dukiyarsu don isar musu da saƙo ko yi musu wa’azi, yana daga cikin abubuwan da suke hana mutane karɓar gaskiya.

3. Ba wanda ya san gaibu sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Wajabcin yin haƙuri a kan kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da jure wa tsangwamar maƙiya.

5. Tuba ta gaskiya tana shafe dukkan laifukan da suka gabata, tana kuma daga cikin dalilan da suke sanyawa Allah ya zaɓi bawansa, ya saka shi cikin mutane nagari.

6. Tsananin hassadar kafirai ga Annabi (ﷺ) da muminai.

7. Tabbatar da tasirin hassada da kambun-baka ga wanda ake yi wa hassadar ko kambun-bakan.

8. Kafirai suna musunta annabcin Manzon Allah (ﷺ) tare da cewa sun san gaskiyarsa, amma saboda tsananin hassada da gaba sai suka jefe shi da hauka, don su hana mutane karɓar saƙon da ya zo da shi.

Suratul Kalam (44-52)

فَذَرۡنِي وَمَن يُكَذِّبُ بِهَٰذَا ٱلۡحَدِيثِۖ سَنَسۡتَدۡرِجُهُم مِّنۡ حَيۡثُ لَا يَعۡلَمُونَ ٤٤ وَأُمۡلِي لَهُمۡۚ إِنَّ كَيۡدِي مَتِينٌ ٤٥ أَمۡ تَسۡـَٔلُهُمۡ أَجۡرٗا فَهُم مِّن مَّغۡرَمٖ
مُّثۡقَلُونَ ٤٦ أَمۡ عِندَهُمُ ٱلۡغَيۡبُ فَهُمۡ يَكۡتُبُونَ ٤٧ فَٱصۡبِرۡ لِحُكۡمِ رَبِّكَ وَلَا تَكُن كَصَاحِبِ ٱلۡحُوتِ إِذۡ نَادَىٰ وَهُوَ مَكۡظُومٞ ٤٨ لَّوۡلَآ أَن تَدَارَكَهُۥ

نِعۡمَةٞ مِّن رَّبِّهِۦ لَنُبِذَ بِٱلۡعَرَآءِ وَهُوَ مَذۡمُومٞ ٤٩ فَٱجۡتَبَٰهُ رَبُّهُۥ فَجَعَلَهُۥ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٥٠ وَإِن يَكَادُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَيُزۡلِقُونَكَ بِأَبۡصَٰرِهِمۡ لَمَّا سَمِعُواْ ٱلذِّكۡرَ وَيَقُولُونَ إِنَّهُۥ لَمَجۡنُونٞ ٥١ وَمَا هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ لِّلۡعَٰلَمِينَ ٥٢

44. Saboda haka ka bar Ni da wanda yake ƙaryata wannan Alƙur’ani; ba da daɗewa ba za Mu yi musu talala ta inda ba za su sani ba.

45. Kuma zan saurara musu. Lalle kaidina mai ƙarfi ne.

46. Ko kuwa kana tambayar su wani lada ne, saboda haka biyan (wannan lada) ya yi musu nauyi?

47. Ko kuwa sanin gaibu a wurinsu yake, saboda haka suke rubuto shi?

48. To ka yi haƙuri da hukuncin Ubangijinka, kada ka zama kamar ma’abocin kifi (Yunus) a yayin da ya yi kira, alhali shi yana cike da baƙin ciki.

49. Ba don wata rahama daga Ubangijinsa ta riske shi ba, da an jefar da shi a ƙungurmin daji alhali shi yana abin suka.

50. Sai Ubangijinsa Ya zaɓe shi Ya sanya shi daga (bayi) nagari.

51. Lalle kuma waɗanda suka kafirta sun yi kusa su kayar da kai da kallonsu yayin da suka ji Alƙur’ani, suka kuma riƙa cewa: “Lalle shi tabbas mahaukaci ne!”

52. Shi kuwa (Alƙur’ani) ba wani abu ba ne face gargaɗi ga talikai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) game da ƙaryata Alƙur’ani da kafirai suke yi, da cewa zai yi musu talala, ya riƙa ba su dukiya da ‘ya’ya, domin su ruɗu da haka, su yi zaton babu wata azaba da zai yi musu, alhali kuwa wannan wani shiri ne nasa mai ƙarfi a gare su.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci wani ruɗani ta fuskar kafirai wanda wataƙila ko shi ne ya hana su karɓar gaskiya:
Na ɗaya, ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, ko yana neman wani lada ne a wurinsu game da abin da yake kiran su zuwa gare shi, saboda haka biyan wannan ladan ya yi musu nauyi, don haka suka bijire wa kiransa? Babu shakka ba haka abin yake ba, Manzo (ﷺ) ba ya neman wani lada a wurinsu, to me ya hana su su yi imani da shi?
Na biyu, ko kuma sun san gaibu ne, don haka suke rubuto abin da suke so su yi jayayya da Manzon Allah (ﷺ) da shi da hujjojinsa masu ƙarfi, wannan ya sa ba dole ne su yi imani da shi ba?
Sai kuma ya umarci Manzonsa (ﷺ) da cewa, ya yi haƙuri da hukuncin da Ubangijinsa ya yi na cewa, zai yi musu talala har lokacin damƙar su ya yi, watau ya ci gaba da isar musu da saƙon Allah, kada muzgunawarsu ta hana shi faɗa musu gaskiya, kada kuma ya zama kamar Annabi Yunusa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya yi fushi ya bar mutanensa ya hau jirgin ruwa ya guje musu. Yayin da nauyi ya yi wa jirgin ruwa yawa sai mutanen cikinsa suka yi ƙuri’a a kan wanda ya cancanta su jefa cikin ruwa don rage wa jirgin nauyi, sai ƙuri’a ta faɗa kansa, sai suka jefa shi cikin ruwa, kifi kuma ya haɗiye shi yana abin zargi. Sannan ne ya yi ta kiran Allah yana maƙare da baƙin ciki a cikin duhun kogi da duhun cikin kifi, yana yi wa Allah tasbihi da yin iƙirari na cewa lalle ya aikata laifi, ya zalunci kansa. Sai ko Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karɓi addu’arsa ya tserar da shi daga cikin cikin kifi ya yaye masa damuwarsa, wanda ba don

rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta riske shi ba, da kifin nan ya jefar da shi can cikin wani ƙungurmin daje yana abin suka, to amma sai Ubangijinsa ya zaɓe shi ya sanya shi cikin bayi nagari.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin tsananin gabar mushirikai ga Manzonsa (ﷺ) da muguwar hassadar da ta cika musu zukata har ta bayyana a idanunsu, har saura ƙiris su kayar da Manzon Allah (ﷺ) saboda mugun kallon da suke yi masa da idanuwansu masu cike da hassada, yayin da suka ji yana karanta musu Alƙur'ani, amma saboda tsananin bin son zuciya da bijire wa gaskiya sai suka riƙa cewa, lalle Manzon Allah mahaukaci ne, alhali sun san cewa Alƙur'ani ba wani abu ne ba face wa'azi da faɗakarwa ga talikai mutune da aljannu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama.

2. Kafiran da suka gabata, kamar Adawa da Samudawa su ma sun ƙaryata ranar alƙiyama.

3. Ranar alƙiyama rana ce mai cike da abubuwan ban tsoro masu razana zukata sosai.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yakan hallaka kafirai da nau'o'in azaba daban-daban domin nuna musu isar Kudurarsa da cikar ikonsa.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Adawa uƙubar da ta zarce ta Samudawa, domin su Samudawa ya hallaka su da tsawa a nan take, amma su Adawa aiko musu ya yi da iska mai tsananin sanyi har tsawon kwana takwas a jere.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wulaƙanta Adawa tun a nan duniya, bayan hallakar da su ya bar gawawwakinsu shirga-shirga yashe a ƙasa kamar kututtturen ɗabino.

7. Girman zunubin Fir'auna da al'ummun da suka gabace shi waɗanda suka ƙaryata manzanni da kuma mutanen Annabi Luɗu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

8. Saɓa wa duk wani manzon Allah saɓa wa Allah ne.

9. Duk wata ni'ima da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa iyaye ni'ima ce ga 'ya'yansu, don haka dole ne su ma 'ya'yan su yi wa Allah godiya a kanta.

10. Mai amfana da ayoyin Allah shi ne wanda ya saurare su sauraro na amfana da abin da ya ji.

69-Suratul Haƙka

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Haƙka*', watau an kira ta da kalmar farko da aka buɗe ta da ita.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* ba tare da wani saɓani ba.

3. Adadin Ayoyinta:
Malamai sun haɗu a kan cewa ayoyinta hamsin da biyu ne (52).

4. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta saba'in da bakwai (77) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Mulk*', kafin *'Suratul Ma'arij*'.

5. Babban Jigonta:
Babban jigon wannan Sura shi ne tabbatar da zuwan ranar alƙiyama kamar yadda Alƙur'ani ya yi bayani, tare da yi wa muminai alƙawarin samun farin ciki da yi wa kafirai alƙawarin azaba da baƙin ciki.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:

• Abubuwan ban tsoro da suke cikin ranar alƙiyama da kuma tsoratar da kafirai da ita.
• Tunatar da mushirikai abin da ya samu al'ummun da suka ƙaryata manzanninsu na azaba da nuna musu cewa, su ma idan ba su yi hattara ba hakan zai iya faruwa da su.
• Sakamakon ranar lahira ga muminai da kafirai, kowaɗanne gwargwadon ayyukansa
• Fito da matsayin Alƙur'ani a fili da gaskiyarsa.
• Tsarkake Manzon Allah (ﷺ) daga yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ƙarya da lallashin sa tare da ƙarfafa masa gwiwa.
• Gargaɗin mushirikai game da alƙawarin azaba da Alƙur'ani yake yi musu bayaninta.

Suratul Haƙka (1-12)
ٱلۡحَآقَّةُ ١ مَا ٱلۡحَآقَّةُ ٢ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡحَآقَّةُ ٣ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ وَعَادُۢ بِٱلۡقَارِعَةِ ٤ فَأَمَّا ثَمُودُ فَأُهۡلِكُواْ بِٱلطَّاغِيَةِ ٥ وَأَمَّا عَادٞ فَأُهۡلِكُواْ بِرِيحٖ
صَرۡصَرٍ عَاتِيَةٖ ٦ سَخَّرَهَا عَلَيۡهِمۡ سَبۡعَ لَيَالٖ وَثَمَٰنِيَةَ أَيَّامٍ حُسُومٗاۖ فَتَرَى ٱلۡقَوۡمَ فِيهَا صَرۡعَىٰ كَأَنَّهُمۡ أَعۡجَازُ نَخۡلٍ خَاوِيَةٖ ٧ فَهَلۡ تَرَىٰ لَهُم مِّنۢ
بَاقِيَةٖ ٨ وَجَآءَ فِرۡعَوۡنُ وَمَن قَبۡلَهُۥ وَٱلۡمُؤۡتَفِكَٰتُ بِٱلۡخَاطِئَةِ ٩ فَعَصَوۡاْ رَسُولَ رَبِّهِمۡ فَأَخَذَهُمۡ أَخۡذَةٗ رَّابِيَةً ١٠ إِنَّا لَمَّا طَغَا ٱلۡمَآءُ حَمَلۡنَٰكُمۡ فِي
ٱلۡجَارِيَةِ ١١ لِنَجۡعَلَهَا لَكُمۡ تَذۡكِرَةٗ وَتَعِيَهَآ أُذُنٞ وَٰعِيَةٞ ١٢

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Mai tabbata (watau alƙiyama)

2. Mece ce mai tabbata?

3. Me ya sanar da kai abin da ake kira mai tabbata?

4. Samudawa da Adawa sun ƙaryata mai ƙwanƙwasa (zukata da tsoro).

5. To amma Samudawa sai aka halaka su da tsawa mai tsanani.

6. Adawa kuma sai aka hallaka su da iska mai tsananin sanyi mai ƙarfi.

7. Ya aiko musu da ita dare bakwai da wuni takwas a jere, sai ka riƙa ganin mutane a cikinta matattu a yashe, kai ka ce rarakakkun kututturan dabinai ne (a zube).

8. To shin za ka iya ganin sauran ɓurɓushinsu?

9. Fir’auna kuma da waɗanda suke gabaninsa da (alƙaryar) da aka kifar, sun zo da manyan laifuka.

10. Sai suka saɓa wa Manzon Ubangijinsu, sai Muka ƙama su kamawa mai ƙaruwa.

11. Mu lalle yayin da ruwa ya mamaye ƙomai Mun ɗauke ku a cikin jirgin ruwa.

12. Don Mu sanya shi wa'azi a gare ku, kuma kunne mai kiyayewa ya kiyaye shi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da batun ranar alƙiyama, inda ya kira ta da sunan mai tabbata, domin a cikinta ne abubuwan da mushirikai suke ƙaryatawa, kamar tashi bayan mutuwa da sakamakon Aljanna da wuta da sauran ababan ban tsoro da za su auku su kuma tabbata a zahiri kowa ya gani da idonsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya girmama lamarin wannan rana da cewa, ita wannan mai tabbata ɗin mece ce ita? Kuma me ya sanar da mai karatu abin da ake kira mai tabbata?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ɓangare na labarin kafirai da suka gabata waɗanda suka ƙaryata manzannin Allah, kuma ya saukar musu da azabarsa, kamar Samudawa mutanen Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda suka ƙaryata ranar alƙiyama mai ƙwanƙwasar zukata da matsanancin tsoro. Amma su Samudawa sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su da tsawa mai tsananin gaske. Su kuma Adawa sai ya hallaka su da iska mai tsananin sanyi mai ƙarfin gaske, wadda ya aiko musu da ita har tsawon dare bakwai da wuni takwas wadda ta ƙarar da ilahirinsu, ta bar su matattu a yaryashe a ƙasa ba mai motsi kamar dai rarakakkun kututturan dabinai waɗanda suke zube a ƙasa. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tambaya cewa, ko akwai wani wanda ya ga ɗaya daga cikinsu ya yi saura a bayan ƙasa bayan da Allah ya hallaka su? Babu ko mutum ɗaya da ya rage, duk sun hallaka.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu al’ummu da suka zo bayan Adawa da Samudawa waɗanda su ma suka ƙaryata manzanninsu, kamar Fir’auna wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika masa Annabi Musa da Annabi Haruna ya ƙaryata su. Hakanan akwai wasu al’ummu da suka gabace shi da wasu alƙaryu da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar musu da azaba, watau alƙaryun Annabi Luɗu

(Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda Allah ya kifar da su saboda miyagun laifukansu na shirka da saɓon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, duk waɗannan al'ummu sun saɓa wa manzon da ya aiko musu, sun ƙaryata shi, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kama su da azaba mai ƙaruwa a kan gwargwadon wadda ta isa ta hallaka su, saboda tsananin kafircinsu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani ɓangare na labarin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) watau farkon Manzo da ya aiko duniya wanda mutanensa suka ƙaryata shi, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sako musu ruwan Ɗufana sama da ƙasa ya hallaka su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, yayin da ruwan ya yi sama ya yi toroƙo ya mamaye komai a bayan ƙasa, sai ya ɗauki iyayensu waɗanda suke cikin tsatsonsu a cikin jirgin ruwa wanda Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya sassaƙa da umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), don haka wannan wata ni'ima ce ga duk waɗanda za su zo bayansu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana hikimar yin haka da cewa, don ya sanya wannan jirgin ruwa da labarinsa su zamanto wa'azi mai nuna yadda yake hallaka kafirai ya tserar da muminai, kuma duk wani mai kunnen kiyaye labarai ya kiyaye da wannan labarin, ya zame masa izina.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da busar ƙaho ta biyu a ranar alƙiyama a lokacin duk tsarin gudanar duniya zai rushe.

2. Tabbatar da cikar Kudurar Allah wajen gudanar da duniya a kan wani ingantaccen tsari guda ɗaya sannan da rushe wannan tsarin sanda ya so.

3. Tabbatar da samuwar mala'iku da bayanin ayyukan wasu daga cikinsu, kamar mala'iku takwas masu ɗauke da Al'arshi a ranar alƙiyama.

4. Tabbatar da ɗaukakar Al'arshi a kan dukkan halittun Allah.

Suratul Haƙƙa (13-18)
فَإِذَا نُفِخَ فِي ٱلصُّورِ نَفۡخَةٞ وَٰحِدَةٞ ١٣ وَحُمِلَتِ ٱلۡأَرۡضُ وَٱلۡجِبَالُ فَدُكَّتَا دَكَّةٗ وَٰحِدَةٗ ١٤ فَيَوۡمَئِذٖ وَقَعَتِ ٱلۡوَاقِعَةُ ١٥ وَٱنشَقَّتِ ٱلسَّمَآءُ فَهِيَ يَوۡمَئِذٖ وَاهِيَةٞ ١٦ وَٱلۡمَلَكُ عَلَىٰٓ أَرۡجَآئِهَاۚ وَيَحۡمِلُ عَرۡشَ رَبِّكَ فَوۡقَهُمۡ يَوۡمَئِذٖ ثَمَٰنِيَةٞ ١٧ يَوۡمَئِذٖ تُعۡرَضُونَ لَا تَخۡفَىٰ مِنكُمۡ خَافِيَةٞ ١٨

13. To idan aka busa ƙaho busa ɗaya.

14. Aka kuma ɗaga ƙasa da duwatsu sai aka dandaƙe su dandaƙewa baki ɗaya.

15. To a wannan rana ce mai afkuwa ta afku (watau alƙiyama).

16. Sama kuma ta kekkece, don kuwa a wannan ranar ita mai rauni ce.

17. Mala'iku kuma suna a sasanninta. A wannan ranar kuma (mala'iku) takwas za su ɗauki Al'arshin Ubangijinka a samansu.

18. A wannan ranar ne kuma za a bujuro da ku, ba wani abu naku mai ɓuya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana abubuwan da za su faru yayin da ranar alƙiyama ta tabbata, wadda a cikinta Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai yi wa masu ƙaryata ta hisabi da sakamako cikakke a kan duk ayyukansu. Wannan rana za ta fara lokacin da Mala'ika Israfilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zai yi busa ɗaya a ƙaho, watau busa ta biyu, a lokacin rayukan ɗaukacin halittu za su koma cikin jikkunan masu su, su miƙe su tsaya cirko-cirko a firgice. A lokacin Allah zai ruguje duk tsarin duniya, a ɗaga ƙasa da duwatsu a niƙe su niƙewa ta bai-ɗaya, ƙasa ta koma fili fetal babu tudu babu kwari, duwatsu kuma su rududduge su zama kamar ƙura abar ɗaiɗaitawa. To a wannan ranar ne ranar alƙiyama mai aukuwa ta auku, watau ta tabbata.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana halin da sama za ta kasance a ranar da cewa, za ta kekkece ta yi ƙofofi don saukar mala'iku, domin ita a wannan ranar ta zama mai rauni, bayan a da ta kasance rufi ne mai tsananin ƙarfi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, su kuma mala'iku za su tsaya a gefunan sama suna masu ƙaskantar da kai ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). A wannan rana mai girma mala'iku takwas ne suke ɗauke da Al'arshin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). A ranar za a bujuro da halittu gaba ɗayansu a gaban Allah, su bayyana a fili babu wani wanda zai ɓoye wa Allah, domin ya san komai yana kuma ganin kowa, zai yi wa kowa hisabi, ya saka masa gwargwadon aikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Cikar adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yayin da kowane mutum za a ba shi sakamakon ayyukansa a rubuce, ba tare da an tauye masa ladansa ba ko an ƙara masa laifin da bai aikata ba.

2. Alamar wanda ya rabauta a lahira ya dace da shiga gidan Aljanna, shi ne wanda aka ba shi littafinsa a hannunsa na dama.

3. Duk wani mumini nagari zai yi farin ciki da sakamakonsa a ranar alƙiyama, zai kuma yarda da abin da Allah zai ba shi ba zai raina ba.

4. Kyawawan ayyukan bawa a duniya su ne sanadiyyar shigarsa Aljanna.

Suratul Haƙƙa (19-24)
فَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ فَيَقُولُ هَآؤُمُ ٱقْرَءُوا۟ كِتَٰبِيَهْ ﴿١٩﴾ إِنِّى ظَنَنتُ أَنِّى مُلَٰقٍ حِسَابِيَهْ ﴿٢٠﴾ فَهُوَ فِى عِيشَةٍ رَّاضِيَةٍ ﴿٢١﴾ فِى جَنَّةٍ عَالِيَةٍ ﴿٢٢﴾
قُطُوفُهَا دَانِيَةٌ ﴿٢٣﴾ كُلُوا۟ وَٱشْرَبُوا۟ هَنِيٓـًٔۢا بِمَآ أَسْلَفْتُمْ فِى ٱلْأَيَّامِ ٱلْخَالِيَةِ ﴿٢٤﴾

19. To duk wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na dama zai ce: "Ku karɓi littafina ku karanta.

20. "Lalle ni na tabbata haka zan haɗu da sakamakona."

21. To shi zai zama cikin rayuwa abar yarda.

22. Cikin Aljanna maɗaukakiya.

23. 'Ya'yan itatuwanta dab da dab suke.

24. (A ce da su): "Ku ci ku sha kuna masu farin ciki saboda abin da kuka gabatar a kwanakinku da suka shuɗe (na duniya)."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da bayanin hukuncin da zai zartar ga bayinsa ranar alƙiyama da sakamakon kowanne daga cikinsu, da cewa, duk wanda aka ba shi littafin ayyukansa a hannunsa na dama, to wannan zai cika da farin ciki da annashawa har ma ya dinga nuna wa mutane littafinsa, yana roƙon da su karɓi littafinsa su karanta su ga karramawar da Allah ya yi masa. Har ma da bayyana musu cewa, da ma ya sani kuma ya tabbatar za a sake tashin sa kuma zai haɗu da kyakkyawan sakamakonsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan bawa nasa nagari ɗan Aljanna ne, yana cikin rayuwar da zai yarda ya amince da ita, saboda ta ƙunshi ni'imomi waɗanda ba sa yankewa har abada, domin zai shiga cikin Aljanna maɗaukakiya, cikin manya-manyan gidaje na alfarma, ga gonaki da lambuna kewaye da shi, 'ya'yan itatuwansu kuwa dab da dab suke ba su da wahalar tsinkowa. A nan ne za a riƙa faɗa wa 'yan Aljanna cewa, su ci lafiyayyen abinci su kuma sha daddaɗan abin sha, saboda kyawawan ayyuka da suka gabatar a rayuwarsu ta duniya na salloli da azumi da sadaka da hajji da kyautata wa mutane da nesantar miyagun ayyuka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cikar adalcin Allah yayin da zai ba wa bawansa littafin ayyukansa a hannunsa ya ga komai a rubuce, ya tabbatar da cewa, ba a zalunce shi ba ko kaɗan.

2. Karɓar littafin ayyuka a hannun hagu alama ce ta 'yan wuta.

3. Kafiri a lahira zai shiga tsananin baƙin ciki da nadama da za ta kai har ya fifita mutuwa a kan rayuwa, duk kuwa da matsanancin sonsa ga rayuwa.

4. Idan har manyan kafirai masu dukiya da masu mulki za su shiga tsananin baƙin ciki da nadama a lahira, to kuma yaya ga sauran mabiyansu za su kasance yayin da za su ga shugabanninsu cikin mawuyacin hali, dukiyarsu da mulkinsu ba su tsinana musu komai ba.

5. Babu abin da zai tsare bawa daga azabar Allah sai imani da aiki nagari.

6. Hanyar samun rabauta a lahira abubuwa biyu ne. Na farko, yin imani da Allah da tsarkake bauta gare shi; na biyu, kyautata wa bayin Allah ta duk hanyoyin da suka dace.

Suratul Haƙƙa (25-37)

وَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِشِمَالِهِۦ فَيَقُولُ يَٰلَيْتَنِي لَمْ أُوتَ كِتَٰبِيَهْ ۝٢٥ وَلَمْ أَدْرِ مَا حِسَابِيَهْ ۝٢٦ يَٰلَيْتَهَا كَانَتِ ٱلْقَاضِيَةَ ۝٢٧ مَآ أَغْنَىٰ عَنِّي مَالِيَهْ ۝٢٨
هَلَكَ عَنِّي سُلْطَٰنِيَهْ ۝٢٩ خُذُوهُ فَغُلُّوهُ ۝٣٠ ثُمَّ ٱلْجَحِيمَ صَلُّوهُ ۝٣١ ثُمَّ فِي سِلْسِلَةٍ ذَرْعُهَا سَبْعُونَ ذِرَاعًا فَٱسْلُكُوهُ ۝٣٢ إِنَّهُۥ كَانَ لَا يُؤْمِنُ بِٱللَّهِ
ٱلْعَظِيمِ ۝٣٣ وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلْمِسْكِينِ ۝٣٤ فَلَيْسَ لَهُ ٱلْيَوْمَ هَٰهُنَا حَمِيمٌ ۝٣٥ وَلَا طَعَامٌ إِلَّا مِنْ غِسْلِينٍ ۝٣٦ لَّا يَأْكُلُهُۥٓ إِلَّا ٱلْخَٰطِـُٔونَ ۝٣٧

25. Amma kuma wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na hagun sai ya ce: "Kaicona, ina ma da ba a ba ni littafina ba!

26. "Kuma ban san mene ne sakamakona ba.

27. "Kaiconta (watau mutuwa), ina ma da ta zama ita ce ƙarshe!

28. "Dukiyata ba ta wadata min komai ba.

29. “Mulkina ya ɓace min da gani.”

30. (Sai a ce da mala’iku): Ku kama shi ku ƙuƙunce shi!

31. Sannan ku shigar da shi (wutar) Jahimu.

32. Sannan ku sa shi cikin sarƙa mai tsawo kamu saba’in.

33. Lalle shi ya kasance ba ya imani da Allah Mai girma.

34. Ba ya kuma kwaɗaitarwa bisa ciyar da mabuƙaci.

35. To a yau ba shi da wani masoyi a nan.

36. Kuma ba shi da wani abinci sai na mugunyar ‘yan wuta.

37. Ba mai cin ta sai masu laifukan ganganci.

A waɗannan ayoyi kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon wanda za a ba shi littafin ayyukansa a hannunsa na hagu, to wannan kam zai cika da baƙin ciki da nadama har ma ya riƙa cewa, ina ma ba a ba shi littafin ayyukansa ba, saboda abin da zai gani a ciki na miyagun ayyukan da ya aikata, waɗanda za su jawo masa azabar Allah da hushinsa. Ya kuma riƙa burin ina ma a ce bai san yadda za a yi masa hisabi ba har a nuna masa sakamakonsa. Kai ina ma a ce, mutuwar da ya yi ita ce ƙarshensa, ba za a sake tashin sa ba bayanta.
Sannan kuma ya shiga nadama game da sakacin da ya yi a duniya ya yi watsi da aikin alheri ya rungumi abin da zai cutar da shi a lahira, ya yi ta hanƙoron tara dukiya da taskake ta a duniya, ga shi a lahira ba ta amfana masa komai ba. Ga shi kuma ya rasa wata hujja ko wani ƙarfi da mulki da zai kare shi daga azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Hakanan zai yi ta yin sambatu marar amfani, daga ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mala’iku masu tsaron wuta da su damƙe shi su haɗa hannayensa da wuyansa su ɗaure tamau sannan su jefa shi cikin wutar Jahimu, don ya ɗanɗani ƙunarta bayan sun ɗaure shi da sarƙa mai tsawon kamu saba’in ba tare da wani sassauci ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu miyagun ayyukan wannan bawa a duniya waɗanda suka jawo masa wannan mummunan sakamako. Ga shi dai bai yi imani da Allah mai girma ba balle ya bauta masa, sannan ya ƙaryata manzannin Allah da gaskiyar da suka zo masa da ita. Har ila yau kuma ba shi da tausayi ko kaɗan a zuciyarsa, domin ba ya tallafa wa mabuƙata kuma ba ya barin wani ya tallafa musu ballantana har ya kwaɗaitar da wani a kan haka. Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, a ranar lahira wannan mutum ba shi da wani makusanci da zai kare shi daga azabar Allah ko ya cece shi a wurin Allah. Kuma a zamansa na cikin wuta ba ya da wani abinci da zai ci in ban da mugunyar abokansa ‘yan wuta, shi kuwa wannan abinci babu mai cin sa sai masu laifuka irin nasa, waɗanda suka kauce wa tafarki madaidaici, suka bi tafarkin ‘yan wuta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rantsuwar da ta fi kowace rantsuwa gamewa a cikin Alƙur’ani ita ce wadda ta ƙunshi komai da komai wanda ake gani da wanda ba a gani na ƙasa da na sama, na halittun Allah da shi kansa mahalicci da siffofinsa.

2. Tsarkake Alƙur’ani daga kasancewa waƙa ko maganar bokaye da tabbatar da cewa, shi maganar Allah ce mai girma da buwaya.

3. Annabi Muhammadu (ﷺ) shi Manzo ne na Allah mai isar da wahayin da Allah ya yo masa zuwa ga bayinsa, kuma mai daraja ne, ba zai zama boka ko mawaƙi ba.

Suratul Haƙka (38-43)
فَلَآ أُقۡسِمُ بِمَا تُبۡصِرُونَ ٣٨ وَمَا لَا تُبۡصِرُونَ ٣٩ إِنَّهُۥ لَقَوۡلُ رَسُولٖ كَرِيمٖ ٤٠ وَمَا هُوَ بِقَوۡلِ شَاعِرٖۚ قَلِيلٗا مَّا تُؤۡمِنُونَ ٤١ وَلَا بِقَوۡلِ كَاهِنٖۚ قَلِيلٗا مَّا تَذَكَّرُونَ ٤٢ تَنزِيلٞ مِّن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٤٣

38. Ina yin rantsuwa da abin da kuke gani.

39. Da kuma abin da ba kwa gani.

40. Lalle shi (Alƙur’ani) tabbas zance ne na wani manzo mai girma.

41. Shi kuwa ba zancen mawaƙi ba ne. Kaɗan ne ƙwarai kuke yin imani.

42. Ba kuma zance ne na boka ba. Kaɗan ne ƙwarai kuke wa’azantuwa.

43. Shi saukakke ne daga Ubangijin halittu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da duk abin da halittu kan iya gani da ma wanda ba sa iya gani, waɗannan abubuwa sun ƙunshi ɗaukacin halittarsa har da shi kansa mahaliccin komai, don ya tabbatar da gaskiyar Manzon Allah (ﷺ) da Alƙur’anin da ya zo da shi cewa, lalle maganar Allah ne wanda kuma Manzon Allah (ﷺ) ya isar wa mutane.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkake Manzonsa (ﷺ) daga duk wata tuhuma da maƙiyansa suke yi masa na cewa, shi mawaƙi ne, alhalin suna ganin Alƙur’ani, su san ba waƙa ba ne, don ba shi da salon zubin waƙa, ba kuma maganar boka ne ba, domin maganar bokaye ta yi hannun-riga da salon Alƙur’ani nesa ba kusa ba. Abin da ya jawo mushirikai suke yi wa Manzon Allah (ﷺ) irin waɗannan tuhumce-tuhumce na banza shi ne rashin imaninsu da rashin wa’azantuwarsu, domin da sun yi imani, sun yi tunani game da kyawawan halayen Manzon Allah (ﷺ) da sun tabbatar da cewa, Alƙur’ani ba ƙirƙirarsa ba ne, saukakke ne daga Allah Ubangijin halittu gaba ɗaya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da gaskiyar Manzon Allah (ﷺ) da tsarkake shi daga yi wa Allah ƙarya.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) mai cikakkiyar hikima ne, daga cikin hikimarsa kuma ba zai taɓa raga wa duk wani mai yi masa ƙarya yana da’awar cewa Allah ne ya aiko shi ba, kuma ya halatta masa jini da dukiyar duk wanda ya bijire masa, shi da mabiyansa kuma su ne za su tsira, waɗanda ba su bi shi ba kuma duka halakakku ne. Irin wannan babban maƙaryaci Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya ƙyale shi ya ci gaba da ƙarairayi da sunansa, ba tare da ya wulaƙanta shi a rayuwarsa ba. To idan har Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya goyi bayan Manzonsa (ﷺ) ya ba shi mu’ujizoji da ayoyi bayyanannu, ya kuma ba shi nasara ya ɗora shi a kan maƙiyansa, to wannan babbar shaida ce da take nuna cewa lalle shi Manzon Allah ne ba ƙarya yake yi wa Allah ba.

3. Babban haɗarin yi wa Allah ƙarya da girman uƙubar mai ƙaga maganar ƙarya ya dangana wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Yayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nufi yi wa wani azaba babu wanda ya isa ya ba shi kariya.

5. Masu taƙawa su ne kawai masu amfana da Alƙur'ani.

Suratul Haƙƙa (44-52)

وَلَوْ تَقَوَّلَ عَلَيْنَا بَعْضَ ٱلْأَقَاوِيلِ ﴿٤٤﴾ لَأَخَذْنَا مِنْهُ بِٱلْيَمِينِ ﴿٤٥﴾ ثُمَّ لَقَطَعْنَا مِنْهُ ٱلْوَتِينَ ﴿٤٦﴾ فَمَا مِنكُم مِّنْ أَحَدٍ عَنْهُ حَٰجِزِينَ ﴿٤٧﴾ وَإِنَّهُۥ لَتَذْكِرَةٌ
لِّلْمُتَّقِينَ ﴿٤٨﴾ وَإِنَّا لَنَعْلَمُ أَنَّ مِنكُم مُّكَذِّبِينَ ﴿٤٩﴾ وَإِنَّهُۥ لَحَسْرَةٌ عَلَى ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٥٠﴾ وَإِنَّهُۥ لَحَقُّ ٱلْيَقِينِ ﴿٥١﴾ فَسَبِّحْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلْعَظِيمِ ﴿٥٢﴾

44. Kuma da ya ƙaga Mana wasu maganganu.

45. Tabbas da Mun kama shi da ƙarfi.

46. Sannan da Mun yanke masa jijiyar zuciyarsa.

47. Sannan kuma ba wani ɗaya daga cikinku da zai kare shi.

48. Lalle shi (Alƙur'ani) wa'azi ne ga masu kiyaye dokokin Allah.

49. Lalle kuma Mu Muna sane da cewa a cikinku akwai masu ƙaryatawa.

50. Kuma lalle shi tabbas nadama ce ga kafirai.

51. Kuma lalle shi tabbas gaskiya ce ta sakankancewa.

52. Saboda haka ka yi tasbihi da sunan Ubangijinka Mai girma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar wa kafirai cewa, lalle Alƙur'ani maganarsa ce, ba Manzon Allah ne ya ƙirƙiro shi ya danganta shi da Allah ba, domin kuwa da a ce ya ƙirƙiri wasu zantuka na ƙarya ya jingina wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) to tabbas da ya yi masa matsanancin kamu, sannan da ya tsinke masa jijiyar zuciyarsa nan take ya hallaka, kuma ba za a sami wani mutum ɗaya wanda zai iya kare shi daga uƙubar Allah ba, don haka babu yadda za a yi ya ƙagi ƙarya ga Allah saboda wasu mutane waɗanda ba za su iya ba shi wata kariya daga azabar Allah ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, shi Alƙur'ani wa'azi ne ga mutane masu kiyaye dokokinsa, masu bin umarninsa, masu guje wa haninsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, yana sane lalle a cikinsu akwai masu ƙaryata Alƙur'ani, to masu yin haka su sani cewa, tabbas wannan ƙaryatawar tasu za ta zame musu babbar nadama a ranar alƙiyama. Sannan su sani cewa, lalle Alƙur'ani gaskiya ce tabbatacciya wadda babu sofanen ƙarya a cikinta, domin daga Allah yake. Sai kuma a ayar ƙarshe Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya yi masa tasbihi, ya tsarkake sunan Ubangijinsa mai girma daga duk wata tawaya ko wani aibu

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da gaskiyar tashin alƙiyama da azabar da take cikinta ga kafirai masu ƙaryata ta.

2. Kafirai su daina gaggauto da azabar Allah a kansu, domin idan ta zo babu mai iya kare su daga gare ta.

3. Da kafirai sun san Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da siffofinsa da girman Kudurarsa da cikar ikonsa kamar yadda ya kamata, da ba su riƙa gaggauto da azabar Allah ba.

4. Tabbatar da ɗaukakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) a saman halittunsa.

5. Gwargwadon tsawon yinin ranar lahira shekara dubu hamsin, wannan ana nufin a wurin kafiri ne, amma shi mumini ba zai ga tsawonta haka ba, kamar yadda ya zo a hadisi cewa, za a sassauta masa tsawon wannan ranar har ya gan ta kamar gwargwadon lokacin da zai sallaci sallar farilla a duniya. [Dubi, Ahmad #11717].

6. Falalar kyakkyawan haƙuri, wanda shi ne haƙurin da babu raki ko kokawa a cikinsa.

7. Annabi (ﷺ) bawa ne na Allah, ana yi masa umarni da hani kamar sauran bayin Allah.

70-Suratul Ma’arij

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
An fi sanin wannan Sura da suna *‘Suratul Ma’arij’*, amma a cikin littattafan hadisi da wasu littattafan tafsiri an kira ta da *‘Suratu Sa’ala Sa’il’*, watau da kalmomin da aka buɗe farkonta da su, domin ba su zo a ko’ina a Alƙur’ani ba sai a cikinta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce Makkiyya, babu wani saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta saba’in da takwas (78) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta kuma sauka bayan ‘*Suratul Hakka’*, kafin *‘Suratun Naba’i’.*

4. Adadin Ayoyinta:
A wurin yawancin malamai adadin ayoyinta arba’in da huɗu ne (44) amma a wurin mutanen Sham arba’in da uku ne (43).

5. Babban Jigonta:
Tana tabbatar da cewa, a ranar alƙiyama lalle kafirai za su gamu da azabar Allah, muminai kuwa za su rabauta da ni’imar Aljanna.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tsoratar da kafirai azabar ranar alƙiyama da tabbatar da zuwanta da bayanin abubuwan ban tsoro da suke cikinta.
• Bayanin siffofin ɗaukaka na Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Tsananin azabar Jahannama da abubuwan da suke jawo a shige ta.
• Bayanin ayyukan muminai waɗanda a dalilinsu Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba su gidan Aljanna.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da ƙarfafa masa gwiwa game da muzgunawar da mushirikai suke yi masa.
• Bayanin kyawawan halaye da Musulunci ya ɗora Musulmi a kansu tare da tsoratar da kafirai da cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai iya kawar da su ya kawo wasu mutanen a madadinsu.

Suratul Ma’arij (1-7)
سَأَلَ سَآئِلٌۢ بِعَذَابٍ وَاقِعٍ ۝١ لِّلْكَٰفِرِينَ لَيْسَ لَهُۥ دَافِعٌ ۝٢ مِّنَ ٱللَّهِ ذِى ٱلْمَعَارِجِ ۝٣ تَعْرُجُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ إِلَيْهِ فِى يَوْمٍ كَانَ مِقْدَارُهُۥ خَمْسِينَ أَلْفَ سَنَةٍ ۝٤ فَٱصْبِرْ صَبْرًا جَمِيلًا ۝٥ إِنَّهُمْ يَرَوْنَهُۥ بَعِيدًا ۝٦ وَنَرَىٰهُ قَرِيبًا ۝٧

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Mai tambaya ya yi tambaya game da wata azaba mai aukuwa.

2. Ga kafirai (wadda) ba ta da wani mai kaɗe ta.3. Daga Allah Mai matattakalai.

4. Mala’iku tare da Jibrilu suna hawa zuwa gare Shi a cikin wata rana (wadda) gwargwadonta yake daidai da shekara dubu hamsin.

5. Sai ka yi haƙuri kyakkyawan haƙuri.

6. Lalle su suna ganin ta mai nisa ce.

7. Mu kuma Muna ganin ta kusa-kusa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da bayanin izgili da mushirikai suke yi wa Manzon Allah (ﷺ) dangane da ranar lahira da azaba da yake faɗa musu cewa za ta same su in ba su yi imani ba, har ta kai saboda tsananin izgili da rashin kunya wani kafiri mai suna Nadru ɗan Haris ya riƙa cewa, idan da gaske ne Alƙur’ani daga Allah yake, to Allah ya yi musu ruwan duwatsu daga sama. [Dubi *Suratul Anfal*, aya ta 32 da Nasa’i, *As-Sunan Al-Kubra* #11556].
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, babu makawa wannan azabar sai ta auku a kan kafirai a ranar alƙiyama, kuma babu mai iya ba su kariya daga gare ta, domin azaba ce daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda ya siffantu da siffar ɗaukaka da manyan darajoji da ni’imomi masu tarin yawa. Mala’ikunsa tare da Mala’ika Jibrilu kuma suna hawa sama zuwa gare shi don cika umarninsa da zartar da tsare-tsarensa a ranar alƙiyama wadda rana ce mai tsawon gaske, gwargwadon tsawonta shekara dubu hamsin ne.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) tare sa umartar sa da yin kyakkyawan haƙuri, kada ya bayyana ƙosawarsa ko damuwarsa a fili, watau ya ci gaba da kiran mutanensa zuwa ga Allah da bauta masa shi kaɗai. Ya bayyana masa cewa mutanensa mushirikai suna ganin nisar azabar Allah, watau a ganinsu ba ma za ta same su ba sam, amma shi Allah mai girma da buwaya yana ganin ta kurkusa, za kuma ta auku babu makawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rugujewar tsarin duniya lokacin zuwan alƙiyama.

2. Girman Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda zai canja komai cikin ƙanƙanin lokaci.

3. A lahira kowanne mutum ta kansa yake yi, wani makusanci ba zai amfanar da makusancinsa da komai ba.

4. Munin ɗabi’ar haɗama da ta rowa.

Suratul Ma’arij (8-18)
يَوۡمَ تَكُونُ ٱلسَّمَآءُ كَٱلۡمُهۡلِ ٨ وَتَكُونُ ٱلۡجِبَالُ كَٱلۡعِهۡنِ ٩ وَلَا يَسۡـَٔلُ حَمِيمٌ حَمِيمٗا ١٠ يُبَصَّرُونَهُمۡۚ يَوَدُّ ٱلۡمُجۡرِمُ لَوۡ يَفۡتَدِي مِنۡ عَذَابِ يَوۡمِئِذِۭ بِبَنِيهِ ١١ وَصَٰحِبَتِهِۦ وَأَخِيهِ ١٢ وَفَصِيلَتِهِ ٱلَّتِي تُـٔۡوِيهِ ١٣ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا ثُمَّ يُنجِيهِ ١٤ كَلَّآۖ إِنَّهَا لَظَىٰ ١٥ نَزَّاعَةٗ لِّلشَّوَىٰ ١٦ تَدۡعُواْ مَنۡ أَدۡبَرَ وَتَوَلَّىٰ ١٧ وَجَمَعَ فَأَوۡعَىٰٓ ١٨

8. A ranar da sama za ta kasance kamar narkakkiyar dalma.

9. Duwatsu kuma su zama kamar kaɗaɗɗiyar auduga (ta gashin tumaki).

10. Kuma aboki ba ya tambayar aboki.

11. (Alhali kuma) ana nuna musu junansu. Mai laifi ya riƙa burin ina ma zai fanshi kansa daga azabar wannan rana da ‘ya’yansa.

12. Da matarsa da ɗan’uwansa.

13. Da danginsa waɗanda suke kare shi.

14. Da ma duk wanda yake a bayan ƙasa baki ɗaya, sannan (fansar) ta tserar da shi.

15. Faufau! Lalle ita (wutar) Laza ce.

16. Mai ɗaɗɗaye fatar kai.

17. Tana kiran wanda ya juya ya ba da baya.18. Ya kuma tara (dukiya) sai ya ɓoye (ta).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu lamura da za su faru a ranar alƙiyama lokacin da sama za ta tsattsage ta zama kamar narkakkiyar dalma ko tagulla, duwatsu kuma su zama kamar kaɗaɗɗiyar audugar gashin tumaki. A ranar kowa zai kiɗime yana ta kansa; wani makusanci ba zai tambayi halin da makusancinsa yake ciki ba; a ranar ne mutum zai ga ɗan’uwansa makusanci ya gane shi sarai, amma ba wanda zai tsaya tambayar abin da ɗan’uwansa yake ciki don tsananin tsoro da firgita. A ranar kafiri zai yi burin ina ma a ce zai iya ba da ‘ya’yansa ya fanshi kansa da su daga azabar Allah, ko ya fanshi kansa da matarsa ko ɗan’uwansa, ko kuma da danginsa na kusa waɗanda suke tsaya masa lokacin da ya shiga cikin wasu wahalhalu; kai ko ma ya fanshi kansa da duk waɗanda suke a bayan ƙasa mutane da aljannu da dabbobi da sauransu, domin shi dai ya samu ya kuɓuta daga azabar wuta.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar masa da martani cewa, abin ba haka yake ba, babu mai iya amfana masa komai daga duk waɗanda ya ambata, domin kuwa wannan azabar da yake gani azaba ce ta wutar Laza mai tsananin ruruwa, mai ɗaɗɗaye fatar kai saboda tsananin zafi, za ta riƙa kiran duk wanda ya juya wa gaskiya baya ya bijire wa bautar Allah shi kaɗai; babu abin da ya sanya a gaba a rayuwarsa ta duniya sai tara dukiya da ɓoye ta ba tare da ya amfanar da kowa da ita ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An halicci ɗan’adam da yawan rashin nutsuwa da karayar zuciya, idan aka jarrabe shi da wata cuta sai ya dinga raki, ya kasa haƙuri, idan kuma wani alheri ne ya same shi sai ya zamo mai tsananin maƙo da rowa, wannan kuma shi ne yake zama sanadiyyar yawan aikata laifi da kauce wa hanyar Allah.

2. Babbar mafita daga miyagun ɗabi’u da munanan ayyuka ita ce tsai da salla, da ita ne kuma mutum yake kare kansa daga shiga wutar Jahannama.

3. Falalar dawwama a kan tsayar da salla da kiyaye ta a kan lokacinta.

4. Salla da sadaka suna cikin mafiya ayyukan ƙwarai da mutum zai aikata.

5. Tsoron azabar Allah yana daga cikin abubuwan da suke sanya bawa kyautata ayyukansa.

6. Wajabcin suturce al'aura ga namiji da mace, sai tsakanin miji da matarsa ko da saɗakarsa.

7. Cika alƙawari da riƙon amana suna daga cikin kyawawan siffofin muminai.

8. Wajabcin bayar da shaida yadda take, domin yin haka yana daga cikin ayyukan mumini.

9. Aljanna tana kasancewa ne ga mutanen da suka kyautata ayyukansu a duniya.

10. 'Yan Aljanna za su samu karramawa ta alfarma a gidan Aljanna yayin da mala'iku za su yi ta haba-haba da su.

Suratul Ma'arij (19-35)

*إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ خُلِقَ هَلُوعًا ١٩ إِذَا مَسَّهُ ٱلشَّرُّ جَزُوعًا ٢٠ وَإِذَا مَسَّهُ ٱلۡخَيۡرُ مَنُوعًا ٢١ إِلَّا ٱلۡمُصَلِّينَ ٢٢ ٱلَّذِينَ هُمۡ عَلَىٰ صَلَاتِهِمۡ دَآئِمُونَ ٢٣ وَٱلَّذِينَ
فِيٓ أَمۡوَٰلِهِمۡ حَقّٞ مَّعۡلُومٞ ٢٤ لِّلسَّآئِلِ وَٱلۡمَحۡرُومِ ٢٥ وَٱلَّذِينَ يُصَدِّقُونَ بِيَوۡمِ ٱلدِّينِ ٢٦ وَٱلَّذِينَ هُم مِّنۡ عَذَابِ رَبِّهِم مُّشۡفِقُونَ ٢٧ إِنَّ عَذَابَ رَبِّهِمۡ
غَيۡرُ مَأۡمُونٖ ٢٨ وَٱلَّذِينَ هُمۡ لِفُرُوجِهِمۡ حَٰفِظُونَ ٢٩ إِلَّا عَلَىٰٓ أَزۡوَٰجِهِمۡ أَوۡ مَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُهُمۡ فَإِنَّهُمۡ غَيۡرُ مَلُومِينَ ٣٠ فَمَنِ ٱبۡتَغَىٰ وَرَآءَ ذَٰلِكَ
فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡعَادُونَ ٣١ وَٱلَّذِينَ هُمۡ لِأَمَٰنَٰتِهِمۡ وَعَهۡدِهِمۡ رَٰعُونَ ٣٢ وَٱلَّذِينَ هُم بِشَهَٰدَٰتِهِمۡ قَآئِمُونَ ٣٣ وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَلَىٰ صَلَاتِهِمۡ يُحَافِظُونَ ٣٤
أُوْلَٰٓئِكَ فِي جَنَّٰتٖ مُّكۡرَمُونَ ٣٥

19. Lalle mutum an halicce shi mai rashin nutsuwa ne.

20. (Watau) idan sharri ya same shi ya zama mai raki.

21. Idan kuma alheri ya same shi ya zama mai maƙo.

22. Sai dai masallata.

23. Waɗanda suke masu dawwama a kan sallarsu.

24. Waɗanda kuma suke akwai haƙƙi sananne a cikin dukiyoyinsu.

25. Ga mai roƙo da wanda ake hana wa (saboda ba ya roƙo).

26. Waɗanda kuma suke gaskata ranar sakamako.

27. Waɗanda kuma suke tsoron azabar Ubangijinsu.

28. Lalle azabar Ubangijinsu ba abar amincewa ba ce.

29. Waɗanda kuma suke kiyaye al'aurarsu (daga yin zina).

30. Sai a wajan matayensu ko kuma ƙwarƙarorinsu; to su a nan ba ababen zargi ba ne.

31. To duk wanda ya nemi (wani abu) bayan wannan, to waɗannan su ne masu ƙetare iyaka.

32. Waɗanda kuma suke kiyaye amanoninsu da alƙawuransu.

33. Waɗanda kuma suke tsai da shaidarsu.

34. Waɗanda kuma suke kiyaye sallolinsu.

35. Waɗannan su ne waɗanda ake girmamawa cikin gidajen Aljanna.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wasu munanan ɗabi'u da ya halicci jinsin mutum da su da kuma hanyar magance su, inda ya tabbatar da cewa, ya halicci ɗan'adam mai rashin nutsuwa ne da saurin karayar zuciya, watau idan wani sharri ya same shi, kamar rashin lafiya ko talauci, to sai ya zamanto mai yawan raki, idan kuma wani abin alheri ne ya same shi, kamar wadata ko yalwa, to sai ya zama mai maƙo, ba ya ciyar da dukiyarsa don Allah, don tsoron talaucewa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci waɗanda za a kuɓutar daga waɗannan munanan halaye, su ne masu tsai da salla, waɗanda ya siffanta su da siffofi takwas :
Na ɗaya, su ne masu dimantar sallolinsu na farilla, babu abin da yake ɗauke musu hankali a kansu, suna yin su a lokutansu ƙayyadaddu.
Na biyu, su ne waɗanda suke akwai haƙƙi sananne a cikin dukiyoyinsu, watau na zakka da sadaka, suna kuma bayar da shi ga wanda ya roƙe su da ma wanda ya rasa amma bai roƙa ba.
Na uku, su ne waɗanda suke gaskata zuwan ranar alƙiyama sanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai saka wa kowa gwargwadon aikinsa.
Na huɗu, su ne masu tsoron azabar Ubangijinsu tare da cewa sun yi ayyuka kyawawa, domin azabar Allah abin tsoro ce, duk mai hankali ba zai aminta daga gare ta ba.
Na biyar, su ne waɗanda suke kiyaye al'aurarsu, ba sa kusantar zina da sauran ayyukan alfasha. Sun taƙaita kawai a kan abin da Allah ya halatta musu na matayensu na aure ko kuma saɗakunsu waɗanda suka mallaka ta hanyar da shari'a ta amince. To idan sun kusanci waɗannan domin biyan buƙatarsu, su kam ba ababan zargi ba ne, domin Allah ya halatta musu su. Amma duk wani wanda ya nemi biyan buƙatarsa ba ta hanyar waɗannan ba, to waɗannan su ne masu ƙetare iyakar Allah, masu auka wa haramun.
Na shida, su ne waɗanda suke kiyaye amanar da aka ba su ta dukiya ko ta wani sirri, suke kuma kiyaye duk wani alƙawari da aka ƙulla da su, ba sa cin amana, ba sa kuma karya alƙawari.
Na bakwai, su ne masu tsayawa su bayar da shaidarsu yadda ya dace, ba tare da la'akari da kusanci ko gaba ba.
Na takwas, su ne masu kiyaye sallolinsu, suna yin su a kan lokutansu tare da cikakkiyar ɗahara da nutsuwa, babu kuma abin da yake shagaltar da su har ya ɗauke musu hankali.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, masu waɗannan siffofi su ne waɗanda za a karrama su a gidajen Aljanna, inda za a sanya su a cikin ni'ima ta har abada, su kuma dace da ganin fuskar Ubangijinsu Maɗaukakin Sarki.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ruɗuwar kafirai da tsananin kafircinsu da Allah da Manzonsa (ﷺ).

2. Fitar wa da kafiri tsammanin shiga Aljanna matuƙar dai ya mutu a kan kafirci.

3. Halittar ‘yan’adam ta farko da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi da ruwan maniyyi, wani babban dalili ne a kan yiwuwar tashi bayan mutuwa.

4. Bambanta mahudar rana da mafaɗarta gwargwadon bambancin canjin yanayi na shekara wani ƙaƙƙarfan dalili ne a kan cikar Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da girman hikimarsa wajen tsara gudanar da rana da wata a sararin samaniya.

5. Lallashin Annabi (ﷺ) da kwantar masa hankali da nuna masa cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sane da halin da kafirai suke nuna masa, kuma yana da ikon idan ya ga dama ya canja su da wasu mutanen kirki, domin babu abin da yake gagarar sa, sai dai ya ƙyale su ne saboda wata hikima tasa.

6. Tsoratar da kafirai da nuna musu cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙyale su bai hallaka su gaba ɗaya ba duk da yawan kafircinsu da izgilinsu ga Manzonsa (ﷺ), domin yana so ya yi musu talala ne har zuwa ranar haɗuwarsu a lahira, inda za su haɗu da sakamakon ayyukansu.

7. Tsananin wulaƙanci da ƙaskancin da kafirai za su haɗu da shi a ranar alƙiyama tun daga fitowarsu daga ƙaburburansu har zuwa shigarsu cikin wutar Jahannama.

Suratul Ma’arij (36-44)

فَمَالِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ قِبَلَكَ مُهۡطِعِينَ ٣٦ عَنِ ٱلۡيَمِينِ وَعَنِ ٱلشِّمَالِ عِزِينَ ٣٧ أَيَطۡمَعُ كُلُّ ٱمۡرِيٕ مِّنۡهُمۡ أَن يُدۡخَلَ جَنَّةَ نَعِيمٖ ٣٨ كَلَّآۖ إِنَّا خَلَقۡنَٰهُم مِّمَّا يَعۡلَمُونَ ٣٩ فَلَآ أُقۡسِمُ بِرَبِّ ٱلۡمَشَٰرِقِ وَٱلۡمَغَٰرِبِ إِنَّا لَقَٰدِرُونَ ٤٠ عَلَىٰٓ أَن نُّبَدِّلَ خَيۡرٗا مِّنۡهُمۡ وَمَا نَحۡنُ بِمَسۡبُوقِينَ ٤١ فَذَرۡهُمۡ يَخُوضُواْ وَيَلۡعَبُواْ حَتَّىٰ يُلَٰقُواْ يَوۡمَهُمُ ٱلَّذِي يُوعَدُونَ ٤٢ يَوۡمَ يَخۡرُجُونَ مِنَ ٱلۡأَجۡدَاثِ سِرَاعٗا كَأَنَّهُمۡ إِلَىٰ نُصُبٖ يُوفِضُونَ ٤٣ خَٰشِعَةً أَبۡصَٰرُهُمۡ تَرۡهَقُهُمۡ ذِلَّةٞۚ ذَٰلِكَ ٱلۡيَوۡمُ ٱلَّذِي كَانُواْ يُوعَدُونَ ٤٤

36. To me ya sami waɗanda suka kafirta suke gaggawa zuwa gare ka?

37. Kungiya-ƙungiya, ta damanka da ta hagunka.

38. Yanzu ashe kowane mutum daga cikinsu yana kwaɗayin a shigar da shi Aljannar ni’ima?

39. Faufau! Lalle Mu Mun halitta su daga abin da suka sani.

40. To, ina yin rantsuwa da Ubangijin wuraren hudowar rana da wuraren faɗuwarta, lalle Mu Masu iko ne.

41. A kan Mu musanya wasu fiye da su, kuma Mu ba Masu kasawa ba ne.

42. To ka ƙyale su su kutsa su yi wasa har sai sun haɗu da ranarsu wadda ake yi musu alƙawarinta.

43. A ranar da za su fito daga ƙaburbura a gurguje, kai ka ce su suna gaggawa ne zuwa ga wata tuta (ta matattara).

44. Idanuwansu a ƙasƙance, wulaƙanci ya lulluɓe su. Wannan ne ranar da ake yi musu alƙawarinta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani abin takaici na mushirikan Makka yayin da suke taƙarƙarewa a kan ƙaryata Manzonsa (ﷺ). Sukan yi cincirindo je wajensa ƙungiya-ƙungiya su

kewaye shi ta ko'ina dama da hagu, kamar suna sauraron sa, amma ba sauraro ne na amfanuwa ba, suna dai jin sa ne kawai domin izgili su samu damar ƙaryata shi, har da furta cewa, idan ma da gaske ne akwai lahira, akwai kuma Aljanna, to ai su ne za su riga shigar ta kafin muminai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, faufau wannan ruɗu ne kawai da tsageranci irin nasu. Idan ba haka ba ta yaya ma za a ce, tantagaryar kafiri mai ƙaryata Allah da Manzonsa kuma ya mutu kafiri bai tuba ba, a ce wai shi ne Allah zai mutunta ya shigar da shi Aljannar ni'ima? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar musu wannan tunani da cewa, faufau, wannan ruɗu ne kawai da ƙin gaskiya, alhali sun tabbatar da cewa, Allah ne ya halicce su daga wani wulaƙantaccen ruwa na maniyyi har suka fito duniya suna raunana, ba sa iya amfana wa kansu komai, amma kuma sai ga shi yanzu suna ƙaryata tashi bayan mutuwa. A kan haka Allah ya yi rantsuwa da Zatinsa, cewa shi ne Ubangijin mahudar rana da mafaɗarta, kuma lalle shi mai iko ne a kan ya hallaka su gaba ɗayansu, ya musanya su da wasu da suka fi su alheri waɗanda za su yi masa biyayya. Yin haka kuwa ba abu ne da zai gagare shi ba duk sanda ya so aiwatar da shi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da cewa, ya ƙyale su su yi ta kutsawa cikin ƙarya da ɓarna, su yi ta wasanni a rayuwarsu ta duniya har sai sun haɗu da ranar alƙiyama wadda ake yi musu alƙawarin zuwanta, ranar da za su yi nadama wadda ba za ta yi musu amfani ba. Rana ce da za su fito daga ƙaburburansu a gurguje kamar suna yin tsere zuwa wata tuta; a ranar babu wanda zai iya bijire wa mai kiran sa duk taurin kansa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, za su yi ta gaggawa zuwa tsayuwa gaban Ubangijinsu, idanuwansu a ƙasƙance, wulaƙanci ya lulluɓe su, a lokacin za a tabbatar musu cewa, wannan ita ce ranar da ake ta yi musu alƙawarin zuwanta tun a duniya, amma ba su ɗauka da gaske ne ba, don haka ga shi alƙawarin Allah ya tabbata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da manzancin Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Gargaɗi yakan yi wa mutane amfani ne kafin azabar Allah ta sauka a kansu.

3. Azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) takan saukar wa mutane ne bayan an gargaɗe su, sun kuma bijire wa gargaɗin.

4. Mutanen Annabi Nuhu a lokacin da aka aiko shi su kaɗai ne suke rayuwa a bayan ƙasa, don haka dukkansu suna da dangantaka da shi. Shi ne farkon Manzo da Allah ya aiko duniya.

5. Abin da duk manzanni da annabawa suka zo da shi shi ne Tauhidi, watau kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da bauta da guje wa shirka.

6. Bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba za ta samu ba sai tare da biyayya ga manzannin Allah, domin su ne masu koyar da mutane yadda za su bauta wa Allah.

7. Bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da kiyaye dokokinsa sanadiyya ce ta samun gafarar Allah.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci ɗan'adam da son tsawon rai duk kuwa da tarin matsaloli da ke cikin rayuwar duniya, don haka ake jan hankalinsa da kwaɗaitar da shi tsawon rai idan ya bi umarnin Allah da manzanninsa.

9. Mutuwa wani ƙayyadajjen lokaci ne, idan ya zo ba a jinkirta shi.

10. Falalar ilimi da amfaninsa wajen nusar da bawa game da bin tafarkin Allah.

71-Suratu Nuh

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da suna *'Suratu Nuh*', amma a cikin Sahihul Bukhari ya ambace ta da '*Suratu Inna Arsalna Nuhan'*.
An kira ta da *'Suratu Nuh'* ne saboda daga farkonta har zuwa ƙarshenta tana bayanin ƙissar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ne.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Babu saɓani a kan cewa Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta saba'in da uku (73) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta kuma sauka bayan saukar ayoyi arba'in na farkon '*Suratun Nahli'*, kafin saukar *'Suratuɗ Ɗuri'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ishirin da takwas ne (28) a lissafin mutanen Kufa. A lissafin mutanen Basra da Sham kuwa ayoyinta ishirin da tara ne (29). Amma a wurin mutanen Makka da Madina ayoyinta talatin ne (30) daidai.

5. Babban Jigonta:
Surar tana karantar da masu kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yin haƙuri da juriya wajen da'awarsu da jihadinsu, kamar yadda Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wajen kiran mutanensa zuwa ga imani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Ba wa mushirikai misali da kafiran farko a tarihin kafuwar duniya, watau mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) waɗanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu uƙubar da ta fi kowace uƙuba ta duniya girma, watau nutsar da su cikin ruwan Ɗufana saboda kafircinsu.
• Bayani dalla-dalla game da da'awar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga kaɗaita Allah da watsi da bautar gumaka da gargaɗin da ya yi ta yi wa mutanensa na azaba mai tsanani idan ba su yi imani da Allah ba da kuma tunatar da su ranar alƙiyama.
• Dagewar mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a kan saɓa masa da kafewarsu a kan haɗa Allah da wasu wajen bauta.
• Ambaton sunayen gumakan da mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suke bauta wa ba Allah ba.
• Mummunar addu'ar da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi a kan mutanensa ta cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su baki ɗayansu kada ya bar wani kafiri ɗaya a bayan ƙasa.
• Addu'ar neman gafara da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi wa mutanensa muminai da sauran wasu muminai maza da mata.

Suratu Nuh (1-4)

إِنَّآ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦٓ أَنۡ أَنذِرۡ قَوۡمَكَ مِن قَبۡلِ أَن يَأۡتِيَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١ قَالَ يَٰقَوۡمِ إِنِّي لَكُمۡ نَذِيرٞ مُّبِينٌ ٢ أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُ وَأَطِيعُونِ ٣ يَغۡفِرۡ لَكُم مِّن ذُنُوبِكُمۡ وَيُؤَخِّرۡكُمۡ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمًّىۚ إِنَّ أَجَلَ ٱللَّهِ إِذَا جَآءَ لَا يُؤَخَّرُۖ لَوۡ كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Lalle Mu Mun aika Nuhu zuwa ga mutanensa cewa: “Ka gargaɗi mutanenka tun kafin azaba mai raɗaɗi ta zo musu.”

2. Ya ce: “Ya ku mutanena, lalle ni mai gargaɗi ne mabayyani a gare ku.

3. “Kan ku bauta wa Allah, ku kiyaye dokokinsa, kuma ku bi ni.

4. “Zai gafarta muku zunubanku, Ya kuma jinkirta muku har zuwa wani lokaci iyakantacce. Lalle ajalin Allah idan ya zo ba a saurarawa; da kun kasance kun san (haka).

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da tabbatar wa Manzonsa cewa, lalle ya aiko Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) zuwa ga mutanensa domin ya kira su ya gargaɗe su da azaba mai raɗaɗi idan suka kafe a kan kafircinsu suka ƙi yin imani da shi.

Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bi umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa mutanensa cewa, shi mai bayyana gargaɗi ne a gare su game da azabar Allah da take dakon su har idan ba su tuba suka daina yin shirka ba. Ya kuma umarce su da su bauta wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai, kada su haɗa shi da komai, su kuma kiyaye dokokinsa, su bi umarninsa su kuma guje wa haninsa, su yi wa shi kansa Annabi Nuhu biyayya game da duk abin da yake umartar su da shi na kaɗaita Allah. Ya tabbatar musu cewa, idan har sun yarda da haka, to Allah zai gafarta musu laifukan da ke tsakaninsu da shi, zai kuma ba wa al’ummarsu tsawon rai har zuwa lokacin da ya iyakance musu, ta yadda za su ci gaba da raya ƙasa matuƙar ba su saki hanyarsa ba. Sannan ya jaddada musu cewa, lalle azabar Allah idan ta zo, to ba za a jinkirta ta ba, da sun san da haka da sun yi gaggawar yin imani da tuba zuwa ga Allah, da yin watsi da ayyukan shirka da kafirci da suke kai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dagewa a kan kira zuwa ga Allah da amfani da salon wa’azi daban-daban, muhimmin al’amari ne ga masu wa'azi.

2. Ba ƙarancin wa’azi ko rashin amfani da salon wa’azi ɗaban-daban ne yakan hana mutane su yi imani ba; imani wani abu ne da Allah yake kimsawa a cikin zuciyar wanda ya zaɓa daga bayinsa.

3. Yawan istigfari yana janyo samun ruwan sama da samun haihuwa da yalwar amfanin gona da yalwar dukiya.

4. Mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) mutane ne masu tsananin kafirci da ƙin gaskiya, ga kuma tsananin girman kai.

Suratu Nuh (5-12)

قَالَ رَبِّ إِنِّي دَعَوْتُ قَوْمِي لَيْلًا وَنَهَارًا ۝٥ فَلَمْ يَزِدْهُمْ دُعَآءِيٓ إِلَّا فِرَارًا ۝٦ وَإِنِّي كُلَّمَا دَعَوْتُهُمْ لِتَغْفِرَ لَهُمْ جَعَلُوٓاْ أَصَٰبِعَهُمْ فِيٓ ءَاذَانِهِمْ وَٱسْتَغْشَوْاْ ثِيَابَهُمْ وَأَصَرُّواْ وَٱسْتَكْبَرُواْ ٱسْتِكْبَارًا ۝٧ ثُمَّ إِنِّي دَعَوْتُهُمْ جِهَارًا ۝٨ ثُمَّ إِنِّيٓ أَعْلَنتُ لَهُمْ وَأَسْرَرْتُ لَهُمْ إِسْرَارًا ۝٩ فَقُلْتُ ٱسْتَغْفِرُواْ رَبَّكُمْ إِنَّهُۥ كَانَ غَفَّارًا ۝١٠ يُرْسِلِ ٱلسَّمَآءَ عَلَيْكُم مِّدْرَارًا ۝١١ وَيُمْدِدْكُم بِأَمْوَٰلٍ وَبَنِينَ وَيَجْعَل لَّكُمْ جَنَّٰتٍ وَيَجْعَل لَّكُمْ أَنْهَٰرًا ۝١٢

5. Ya ce: “Ya Ubangijina, lalle ni na kira mutanena dare da rana.

6. “To kiran nawa ba abin da ya ƙara musu sai tawaye.

7. “Lalle ni kuma duk sanda na kira su don Ka gafarta musu, sai su sanya ‘yan yatsunsu a cikin kunnuwansu, su kuma lulluɓu da tufafinsu kuma su kafe (a kan haka), su yi girman kai matuƙar girman kai.

8. “Sannan lalle na yi kiran su da babbar murya.

9. “Sannan lalle na yi musu a bayyane, na kuma yi musu a ɓoye sosai.

10. “Sai na ce: “Ku nemi gafarar Ubangijinku, lalle Shi Ya kasance Mai yawan gafara ne.

11. “Zai saukar muku da ruwan sama mai yawa.

12. “Kuma Ya daɗe ku da dukiyoyi da ‘ya’yaye, Ya kuma sanya muku gonaki Ya kuma gudanar muku da ƙoramu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya kai kukansa zuwa gare shi, yana faɗa masa irin yadda ya duƙufa a kan kiran mutanensa zuwa ga tauhidi da watsi da shirka, ya kuma bi hanyoyi daban-daban wajen yi musu da’awa amma kamar ba ya yi. Ya bayyana wa Allah cewa, ya dimanci kiran su ba dare ba rana, amma maimakon kiransa ya ƙara musu kusanci da Allah sai ma ya ƙara musu bijirewa da yi masa tawaye. Abin har ya kai duk sanda yake yi musu wa’azi, yana kiran su zuwa bautar Allah don su sami gafararsa, sai su toshe kunnuwansu da ‘yan yatsunsu don kada su saurari abin da yake faɗa musu, su kuma rufe fuskokinsu da tufafinsu don kada ma su gan shi, suka doge da ci gaba a kan kafircinsu, girman kansu ya hana su miƙa wuya gare shi.
Sannan Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya bayyana hanyoyi daban-daban da ya bi wajen kiran su zuwa ga Allah; ya bi salon yi musu wa’azi a bayyane kowa yana ji; sannan ya kira su da babbar murya don wanda bai jiyo abin da yake faɗa ba ya ji shi, musamman a wuraren tarukansu da haɗuwarsu, ya kuma bi wasu har gida ya yi musu wa’azi a ɓoye daga shi sai su, watau musamman manyansu waɗanda ba za su saurari gaskiya a bainar jama’a ba.
Haka kuma ya yi amfani da salon kwaɗaitar da su samun ni’imomin rayuwa idan suka yi imani da shi, ya bayyana musu cewa su tuba su nemi gafarar Allah, domin shi Allah mai yawan gafara ne ga duk wanda ya tuba. Ya tabbatar musu da cewa idan sun yi haka, to Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da falalarsa zai saukar musu da ruwan sama mai yawan zuba a kai-a kai duk sanda suka buƙata su samu, don haka ba za su ji tsoron fari ba. Zai kuma ƙara musu yawan dukiya da ‘ya’ya, ya kuma sanya musu gonaki masu yawan ‘ya’yan itatuwa, ya kuma gudanar musu da ƙoramu waɗanda za su riƙa shan ruwansu su kuma shayar da gonakinsu da dabbobinsu. Babu shakka waɗannan muhimman ni’imomi ne da ɗan’adam yake matuƙar buƙata.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittar mutane mataki-mataki, wani ƙaƙƙarfan dalili ne mai nuna cikakkiyar hikimar Allah da faffaɗan iliminsa da kamalar Kudurarsa.

2. Halittar sammai bakwai hawa-hawa ne, ɗaya tana saman ɗaya.

3. Siffanta wata da haske rana kuma da fitila yana nuna cewa hasken wata ba daga jikinsa yake ba; yana samun haskensa ne daga rana, ita kuma rana kamar fitila ce haskenta a jikinta yake tana haskaka duk abin da yake fuskantar ta.

4. Asalin ‘yan’adam duka daga ƙasa ne.

5. Kowane ɗan’adam zai koma cikin ƙasa ne yayin da zai mutu a binne shi a cikin ƙabarinsa, ko wasu ƀangarori nasa su ɗaiɗaitu a sassanta, ko a cikin ruwa.

6. Ranar alƙiyama mutane za su fito ne daga ƙaburburansu domin tsayuwar hisabi.

7. Kasa a shimfiɗe take kamar shimfiɗar barci don ta dace da rayuwar ɗan’adam a kanta, ya sami damar tafiya a kanta cikin sauƙi, ta kuma dace da shuke-shukensa a kanta.

Suratu Nuh (13-20)

مَّا لَكُمۡ لَا تَرۡجُونَ لِلَّهِ وَقَارٗا ١٣ وَقَدۡ خَلَقَكُمۡ أَطۡوَارًا ١٤ أَلَمۡ تَرَوۡاْ كَيۡفَ خَلَقَ ٱللَّهُ سَبۡعَ سَمَٰوَٰتٖ طِبَاقٗا ١٥ وَجَعَلَ ٱلۡقَمَرَ فِيهِنَّ نُورٗا وَجَعَلَ ٱلشَّمۡسَ سِرَاجٗا ١٦ وَٱللَّهُ أَنۢبَتَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ نَبَاتٗا ١٧ ثُمَّ يُعِيدُكُمۡ فِيهَا وَيُخۡرِجُكُمۡ إِخۡرَاجٗا ١٨ وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ بِسَاطٗا ١٩ لِّتَسۡلُكُواْ مِنۡهَا سُبُلٗا فِجَاجٗا ٢٠

13. “Me ya same ku ne ba kwa ganin girman Allah?

14. “Haƙiƙa kuma Ya halicce ku ta mataki-mataki.

15. “Shin ba kwa ganin yadda Allah Ya halicci sammai bakwai rufi-rufi?

16. “Ya kuma sanya wata mai haske a cikinsu; rana kuma Ya sanya ta fitila?

17. “Allah ne kuma Ya tsiro da ku daga ƙasa a tsirowa (ta halitta).

18. “Sannan Ya mayar da ku cikinta, zai kuma fitar da ku haƙiƙar fitarwa.

19. “Kuma Allah Ya sanya muku ƙasa a shimfiɗe.

20. “Don ku riƙa bin manya-manyan hanyoyi a cikinta.”

A waɗannan ayoyi Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ci gaba da jan hankalin mutanensa da nuna musu ƙarfafan hujjoji masu nuna Kudurar Allah da cikar ikonsa da cancantar a bauta masa shi

kaɗai. Ya ja hankalinsu da cewa, me ya sa ba sa ganin girman Allah, ba sa fatan samun ladansa kuma ba sa jin tsoron uƙubarsa, alhali kuwa sun san shi ne ya halicce su mataki bayan mataki, yayin da ya fara halittar babansu Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga ƙasa, sannan ya halicci kowane ɗaya daga cikinsu daga ɗigon maniyyi, sannan ya mayar da shi jini, sannan gudar tsoka, sannan ya zama mutum cikakke. Da haka suka fito duniya suna jarirai har suka yi wayo suka zama cikakkun mutane masu hankali.
Annabi Nuhu kuma ya ja hankalinsu da cewa, ba sa ganin yadda Allah ya halicci sammai bakwai hawa-hawa, wata a saman wata, sannan ya sanya wata a sama mafi kusa ya zama haske mai haskaka doron ƙasa, ita kuma rana ya sanya ta ta zama fitila mai haskaka ko'ina. Su kuma mutane idan suka dubi yanayin halittarsu za su ga shi ne ya halicce su daga ƙasa ta hanyar halittar babansu Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ƙasa, suna kuma cin abin da ƙasar ta tsiro da shi. Bayan mutuwarsu kuma zai mayar da su cikin ƙasar ne har sai lokacin tashin alƙiyama ya yi sai ya fito da su don yi musu hisabi. Don haka Allah shi ne wanda rayuwa da mutuwa suke hannunsa shi ne kuma mai iya tayar da matattu bayan mutuwa.
Allah kuma shi ne wanda ya halitta wa mutane ƙasa a shimfiɗe daidai da yadda za su ji daɗin rayuwa a kanta, ya kuma hore musu bin manya-manyan hanyoyinta masu yalwa don neman arziki na halal.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An bayyana yadda manyan gari suke taka muguwar rawa wajen dulmiyar da mabiyansu, ta hanyar amfani da dukiya da matsayi wajen cim ma muradinsu.

2. Idan kafirai masu dukiya da yawan 'ya'ya, dukiyarsu da 'ya'yansu ba su amfana musu komai ba a wurin Allah sai taɓewa, to ina ga mabiyansu waɗanda suka bi su a kan ɓarna da ɓata suka sallama musu ragamar rayuwarsu.

3. Zunubi ne sanadiyyar hallaka a duniya da azabar lahira bayan mutuwa.

4. Tabbatar da azabar barzahu, watau azabar ƙabari, domin an shigar da mutanen Annabi Nuhu cikin azaba ba tare da jinkiri ba bayan nutsar da su a ruwa.

5. Ishara zuwa ga asalin shirka a bayan ƙasa. Watau shirka ta samo asali ne daga zuzuta girmama wasu bayin Allah salihai, domin gumakan mutanen Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) asalinsu wasu mutane ne nagari waliyyan Allah da ake girmama su. To yayin da suka mutu sai Shaiɗan ya ƙawata wa mutanensu cewa, me zai hana su gina mutum-mutuminsu su ajiye a gidajensu don su riƙa tunawa da su? Bayan sun ji wasiyyar Shaiɗan sun yi hakan da lokaci mai tsawo, sai kuma ya sake dawowa wajen jikokinsu ya nuna musu cewa, ai magabatansu suna bauta wa waɗannan gumaka ne suna neman agaji da taimako daga wajensu, sai suka yarda suka ci gaba da bautar su. [Dubi, Bukhari #4920].

Suratu Nuh (21-25)
قَالَ نُوحٌ رَّبِّ إِنَّهُمْ عَصَوْنِي وَٱتَّبَعُواْ مَن لَّمْ يَزِدْهُ مَالُهُۥ وَوَلَدُهُۥٓ إِلَّا خَسَارًا ﴿٢١﴾ وَمَكَرُواْ مَكْرًا كُبَّارًا ﴿٢٢﴾ وَقَالُواْ لَا تَذَرُنَّ ءَالِهَتَكُمْ وَلَا تَذَرُنَّ وَدًّا وَلَا سُوَاعًا وَلَا يَغُوثَ وَيَعُوقَ وَنَسْرًا ﴿٢٣﴾ وَقَدْ أَضَلُّواْ كَثِيرًا ۖ وَلَا تَزِدِ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا ضَلَٰلًا ﴿٢٤﴾ مِّمَّا خَطِيٓـَٰٔتِهِمْ أُغْرِقُواْ فَأُدْخِلُواْ نَارًا فَلَمْ يَجِدُواْ لَهُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ أَنصَارًا ﴿٢٥﴾

21. Nuhu ya ce, "Ya Ubangijina, lalle su sun saɓa mini, sun kuma bi duk wanda dukiyarsa da 'ya'yansa ba su ƙara masa komai ba sai asara.

22. “Suka kuma shirya makirci babba.

23. “Suka kuma ce: ‘Kada ku bar abubuwan bautarku, kuma lalle kada ku bar *Waddu* da *Suwa’u* da *Yagusu* da Ya’uƙu da *Nasaru*.’

24. “Haƙiƙa kuwa sun ɓatar da adadi mai yawa; kar kuma Ka ƙari kafirai da komai sai ɓata.”

25. Saboda saɓonsu ne aka nutsar da su, sai aka shigar da su wuta, don haka, ba su sami wasu mataimaka ba Allah ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ƙoka wa Ubangijinsa da cewa, wa’azin da ya daɗe shekaru aru-aru yana yi wa mutanensa bai yi musu wani amfani ba, domin sun saba masa sun bijire wa da’awarsa, sun bi wasu manyan mutane masu dukiya waɗanda kuma dukiyarsu da ‘ya’yansu ba su ƙara musu komai ba sai taɓewa da asara, domin kuwa ba abin da suka sa a gaba sai shirya mummunan makirci da yaɗa shirka da saɓon Allah da zuga wawayensu kan kada su kuskura su watsar da bautar gumakansu waɗanda suka gada iyaye da kakanni, musamman gumakan Waddu da Suwa’u da Yagusu da Ya’uƙu da Nasru. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, da irin waɗannan kalaman nasu suka ɓatar da yawancin mutane. Don haka Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙi Allah cewa, muddin dai mutanensa sun zalunci kawunansu sun zaɓi kafewa a kan kafirci da saɓon Allah, to kada ya ƙara musu wani abu sai ɓata da dulmiya cikin kafirci, watau wannan shi ne abin da suka zaba wa kansu da kansu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana uƙubarsu ta duniya da ta lahira, da cewa, saboda miyagun laifukansu na kafirci da bijire wa kiran da Manzonsa Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake yi musu, wannan ya sa ya nutsar da su a ruwan Ɗufana tun a nan duniya, suna hallaka kuwa sai ya shigar da su wata azabar ta wuta ba tare da wani jinkiri ba, don haka ba su samu wasu mataimaka waɗanda ba Allah ba da suka iya kuɓutar da su daga nutsewa a ruwa da shiga wuta bayan mutuwarsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka al’ummarsa bayan ya tabbatar da cewa, babu sauran wanda zai yi imani da Allah kuma.

2. Kamar yadda Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yake tunanin makomar al’ummarsa a nan gaba, watau tsareku masu zuwa, haka yake neman Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗauki matakin ba su kariya daga ɓata da haihuwar tantirai kuma kafirai, hakanan ya wajaba ga duk wani jagora a cikin al’ummarsa ya riƙa tunanin rayuwar tsareku masu tasowa, ya yi aiki tuƙuru don ganin ya gina musu abin da zai tsare maslaharsu ta addini da rayuwa nan gaba.

3. Babu laifi idan mutum zai yi addu’a ya fara da kansa.

4. Addu’ar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ga iyayensa da nema musu gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta nuna cewa sun yi imani, domin da ba su yi imani ba da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hana shi kamar yadda ya hana Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) nema wa babansa gafara saboda ya mutu kafiri.

5. Yawaita istigfari sunna ce ta annabawa.

6. Annabawa bayin Allah ne masu ƙaskantar da kai a gabansa, masu neman gafararsa.

7. Albishir ga duk wani mumini da mumina da cewa, tuni Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya nema masa gafarar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratu Nuh (26-28)

وَقَالَ نُوحٞ رَّبِّ لَا تَذَرۡ عَلَى ٱلۡأَرۡضِ مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ دَيَّارًا ٢٦ إِنَّكَ إِن تَذَرۡهُمۡ يُضِلُّواْ عِبَادَكَ وَلَا يَلِدُوٓاْ إِلَّا فَاجِرٗا كَفَّارًا ٢٧ رَّبِّ ٱغۡفِرۡ لِي وَلِوَٰلِدَيَّ
وَلِمَن دَخَلَ بَيۡتِيَ مُؤۡمِنٗا وَلِلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۗ وَلَا تَزِدِ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا تَبَارٗا ٢٨

26. Nuhu ya ce: “Ya Ubangijina, kada Ka bar wani mutum ɗaya daga kafirai a bayan ƙasa.

27. “Lalle idan har Ka bar su, to za su ɓatar da bayinka, kuma ba za su haifi kowa ba sai fajiri mai tsananin kafirci.

28. “Ya Ubangijina, Ka gafarta min ni da mahaifana da kuma waɗanda suka shiga gidana suna muminai, da kuma (sauran) muminai maza da mata, kada kuma Ka ƙari kafirai da komai sai hallaka.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya roƙe shi da ya hallaka mutanensa bayan ya yi masa wahayi cewa, babu sauran waɗanda za su yi imani da shi bayan ‘yan kaɗan da suka riga suka yi imani, don haka sai ya kira Ubangijinsa ya roƙe shi cewa, kada ya bar wani kafiri ɗaya yana karakaina a bayan ƙasa, domin ya tabbata cewa, idan har Allah ya ƙyale su, to za su ci gaba da ɓatar da bayinsa muminai, kuma nan gaba ba za su ƙara haihuwar wani wanda zai bi Allah ba sai dai su haifi fajiri wanda zai kangare masa, mai tsananin kafirci wanda ba zai gode wa ni’imominsa ba.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya karɓi addu’ar Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya hallakar da mutanensa ta hanyar dulmiyar da su cikin ruwan Ɗufana gaba ɗayansu, ya tserar da Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da waɗanda suka yi imani da shi.
Sai kuma a ayar ƙarshe Annabi Nuhu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ɗaga hannu ya roƙi Ubangijinsa cewa, ya gafarta masa zunubansa, ya kuma gafarta wa mahaifansa biyu da duk wani mumini da ya shiga gidansa, watau ya lizimce shi yana mai imani da shi, ya kuma gafarta wa muminai mazansu da matansu, su kuma azzalumai waɗanda suka cutar da kansu da kafirci da saɓon Allah kada ya ƙara musu komai sai hallaka da asara.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Alƙur’ani littafi ne mai saurin ratsa zuciya ga duk wanda ya tsaya da zuciya ɗaya ya saurare shi, mutum ne shi ko aljani.

2. Aljannu halitta ce da suke a ɓoye, mutum ba ya iya ganin su a siffarsu ta aljannu sai dai su suna ganin kowa, don haka shi kansa Manzon Allah (ﷺ) bai gan su ba lokacin da suke kusa da shi suna sauraron karatunsa na Alƙur’ani har sai da Allah ya yiwo masa wahayi ya sanar da shi.

3. Annabi Muhammad (ﷺ) bawan Allah ne kuma Manzonsa, yana karɓar umarni ne daga Allah mahaliccinsa, yana bin dokarsa.

4. Annabi Muhammad (ﷺ) Manzon Allah ne zuwa ga mutane da aljannu baki ɗaya.

5. Daga cikin aljannu akwai waɗanda suka yi imani da Allah, akwai kuma mushirikai.

6. Waɗannan aljannun da suka saurari karatun Alƙur'ani daga Manzon Allah (ﷺ), wasu aljannu ne da suka fito daga garin *Nasibin* na ƙasar Sham, watau Siriya a yau, kuma suna magana da harshen Larabci ne wanda hakan ya ba su damar fahimtar Alƙur'ani yayin da suka saurari karatunsa.

7. Alƙur'ani littafi ne da yake cike da hikima da fasaha mai ban al'ajabi matuƙa.

8. Alƙur'ani littafin shiriya ne, yana nuna wa mutane da aljannu aƙidu na gaskiya da kyawawan ayyuka da maganganu da halaye.

9. Waɗannan aljannun sun kasance a da mushirikai ne sai bayan sun ji karatun Alƙur'ani ne suka yi imani.

10. Waɗannan aljannun sun nuna kyakkyawar aniyarsu, don haka suka gaskata faɗarsu da aiki, yayin da suka yi alƙawarin cewa ba za su ƙara haɗa wani da Allah ba, bayan da farko sun ce sun yi imani.

11. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsarkaka daga duk wani aibi ko naƙasa, kamar buƙatar mata ko ɗa.

12. Daga cikin aljannu akwai masu cewa Allah yana da mata da ɗa.

13. Daga cikin aljannu akwai maƙaryata, kamar yadda ake da su a cikin mutane.

14. Daga cikin aljannu akwai maza akwai mata.

15. Danganta kowace matsala da aljannu da neman taimako a wurinsu abu ne da yake ƙara sanya su ɗagawa, sai suka sanya rayuwar mutane cikin tsoro da firgici.

16. Neman tsari da aljannu shirka ce kuma haramun ne.

17. Duk wata mummunar aƙida da take cikin mutane akwai irinta a cikin aljannu, hakanan duk wani alheri da ke cikin mutane akwai shi a cikin aljannu.



72-Suratul Jinn

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Jinni*', saboda ta zo da labarin aljannu waɗanda suka saurari karatun Alƙur'ani daga Manzon Allah (ﷺ) suka ba da gaskiya. Imamul Bukhari a cikin ingantaccen littafinsa ya kira ta '*Suratu Kul Uhiya Ilayya*', watau da kalmominta na farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun haɗu a akan cewa Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta arba'in (40) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul A'arafi*', kafin '*Suratu Yasin*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin da takwas ne (28) daidai.

5. Dalilin Saukarta :
An karƀo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Annabi (ﷺ) ya fita tare da wasu sahabbansa suka nufi kasuwar *Ukaz*. A daidai wannan lokacin kuwa an hana shaiɗanu sato labari daga sama, an riƙa jifan su da harshen wuta na taurari. Sai shaiɗanun suka koma wajen jama'arsu, suka tambaye su: "Me ya faru gare ku?" Sai suka ce: "An hana mu sato labari daga sama ne, ana jifan mu da harshen wuta na taurari." Sai 'yan'uwansu suka ce: "Babu abin da ya hana ku samo labari daga sama sai wani babban al'amarin da ya faru, don haka ku bazama ku nufi gabashin duniya da yammacinta, ku duba ku ga mene ne ya hana ku samo labari daga sama?" Sai wasu daga cikinsu suka nufi nahiyar *Tihama* inda Annabi (ﷺ) ya iso wani wuri mai suna '*Nakhla*' za su nufi kasuwar *Ukazu*, ya tsaya yana jan sahabbansa sallar Asuba. Yayin da aljannun nan suka ji ana karanta Alƙur'ani sai suka tsaya suka saurari karatunsa, sai kuwa suka faɗa wa junansu cewa: "Wallahi wannan ne ya hana mu samo labari daga sama." To a nan ne suka juya suka koma zuwa ga jama'arsu suna cewa: "Ya ku jama'armu, lalle mun ji wani abin karatu mai ban mamaki." Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Annabinsa (ﷺ) faɗarsa: "Ka ce: An yiwo min wahayi cewa wata jama'a ta aljannu sun saurari (karatun Alƙur'ani).... an yi masa wahayin maganar aljannun ne kawai." [Ahmad #2271 da Bukhari #773 da 4921 da Muslim #449].

6. Babban Jigonta:
Surar tana tabbatar da cewa, Alƙur'ani gaskiya ne, kuma wahayi ne daga Allah zuwa Manzonsa (ﷺ), aljannu kuma sun yi imani da shi.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:

• Tabbatar da girman matsayin Annabi (ﷺ) da nuna cewa, da'awarsa ba ta tsaya iya mutane ba kaɗai, ta kai har ga aljannu waɗanda su ma sun saurari karatun Alƙur'ani kuma sun fahimce shi, sun kuma fahimci abin da yake koyarwa na Tauhidi da shiriya da sanin girman Allah da tsarkake shi daga a dangana masa mata ko ɗa ko wani abokin tarayya.

• Rushe bautar aljannu da wasu suke yi.

• Rushe bokanci da da'awar sanin gaibi, sai manzannin da Allah ya zaɓa ya sanar da su abin da ya ga dama daga ɓoyayyen iliminsa.

• Tabbatar da samuwar wasu halittun Allah da ake kiran su 'aljannu' waɗanda a cikinsu akwai nagari akwai na banza kashi-kashi.

• Bayanin ɓatar duk masu yi wa Allah ƙarya suna jingina masa abin da bai faɗa ba, da masu bautar aljannu da masu ƙaryata tashi bayan mutuwa da nuna musu cewa, aljannu ba za su iya kuɓuce wa ikon Allah ba.

• Mamakin aljannu na ganin ana jifan su da harshen wuta idan sun nufi sararin sama don su sato labari.

• Sukan mushirikai masu hana a tsarkake Allah da bauta a cikin masallatan Allah da gargaɗin su da cewa, za su yi nadama a kan yunƙurinsu na cutar da Manzon Allah (ﷺ) da sukan addininsa.

Suratul Jinn (1-7)

قُلْ أُوحِيَ إِلَيَّ أَنَّهُ ٱسْتَمَعَ نَفَرٌ مِّنَ ٱلْجِنِّ فَقَالُوٓاْ إِنَّا سَمِعْنَا قُرْءَانًا عَجَبًا ۝١ يَهْدِيٓ إِلَى ٱلرُّشْدِ فَـَٔامَنَّا بِهِۦ ۖ وَلَن نُّشْرِكَ بِرَبِّنَآ أَحَدًا ۝٢ وَأَنَّهُۥ تَعَٰلَىٰ
جَدُّ رَبِّنَا مَا ٱتَّخَذَ صَٰحِبَةً وَلَا وَلَدًا ۝٣ وَأَنَّهُۥ كَانَ يَقُولُ سَفِيهُنَا عَلَى ٱللَّهِ شَطَطًا ۝٤ وَأَنَّا ظَنَنَّآ أَن لَّن تَقُولَ ٱلْإِنسُ وَٱلْجِنُّ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا ۝٥
وَأَنَّهُۥ كَانَ رِجَالٌ مِّنَ ٱلْإِنسِ يَعُوذُونَ بِرِجَالٍ مِّنَ ٱلْجِنِّ فَزَادُوهُمْ رَهَقًا ۝٦ وَأَنَّهُمْ ظَنُّواْ كَمَا ظَنَنتُمْ أَن لَّن يَبْعَثَ ٱللَّهُ أَحَدًا ۝٧

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ka ce: "An yiwo min wahayi na cewa, wata jama'a ta aljannu sun saurari (karatun Alƙur'ani), sai suka ce: "Lalle mu mun ji Alƙur'ani mai ban mamaki.

2. "Yana shiryarwa zuwa ga daidai, saboda haka muka yi imani da shi; ba kuwa za mu haɗa wani da Ubangijinmu ba har abada.

3. "Kuma lalle yadda lamarin yake, girman Ubangijinmu ya ɗaukaka, bai riƙi wata mata ko wani ɗa ba.

4. "Kuma lalle yadda lamarin yake, wani wawa daga cikinmu ya kasance yana faɗar mummunar ƙarya game da Allah.

5. "Lalle kuma mun yi tsammanin mutum da aljan ba za su taɓa faɗar ƙarya game da Allah ba.

6. "Kuma lalle yadda lamarin yake, wasu mazaje daga mutane sun kasance suna neman tsari daga wasu mazaje na aljannu, saboda haka suka ƙara musu girman kai.

7. "Kuma lalle su sun yi tsammanin-kamar yadda kuka yi tsammani-cewar Allah ba zai tashi kowa ba har abada.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da umartar Manzonsa (ﷺ) ya faɗa wa al'ummarsa cewa, an yiwo masa wahayi game da wasu jama'a na aljannu waɗanda suka saurari karatunsa na Alƙur'ani mai girma a wani wuri da ake kira *Baɗnu Nakhla,* lokacin da yake yi wa sahabbansa sallar Asuba. Bayan sun

gama sauraro sai suka koma wajen jama’arsu ta aljannu suna gaya musu cewa, lalle sun saurari wani abin karatu mai ban al’ajabi, yadda yake cike da fasaha da hikima. Yana kuma shiryarwa zuwa ga ingantacciyar aƙida da kyakkyawan aiki da kyawawan maganganu, don haka su sun yi imani da shi, kuma daga lokacin ba za su ƙara haɗa Allah da wani ba wajen bautarsu.
Sun kuma yi imani da cewa, girman Ubangijinsu ya ɗaukaka, bai kuma riƙi wata mata ko ɗa ba, kamar yadda mushirikansu na aljannu da na mutane suke riyawa. Suka kuma tabbatar wa da jama'arsu cewa, maganar da wawan cikinsu yake yi, watau Iblisu da ire-irensa na yi wa Allah ƙarya da jingina masa mata da ɗa mummunar ƙarya ce suke ƙirƙira masa. Suka kuma bayyana cewa, da farko sun zaci mushirikan mutane da na aljannu ba za su taɓa yi wa Allah ƙarya ba ballantana har su riƙa cewa yana da mata da ɗa, wannan ne ya sa har suka ɗauki maganarsu a matsayin gaskiya, sai suka bi su ido-rufe.
Sannan suka bayyana wata mummunar aƙida ta wasu mutane waɗanda, a lokacin jahiliyya idan sun yi tafiya sun sauka a wani wuri mai ban tsoro, kamar wani kwari, sukan nemi tsarin wasu mazajen aljannu, watau ɗayansu yakan ce, yana neman shugaban wannan kwarin ya kare shi daga sharrin wawayen jama’arsa. Wannan lamari ya janyo mazajen mutane suka ƙara firgita da tsorata daga mazajen aljannu. Suka kuma tabbatar wa da jama'arsu cewa, sun gano cewa, kamar yadda su aljannu suka yi zaton babu wanda Allah zai tashe shi domin yi masa hisabi, hakanan su ma mutane suka yi wannan zaton. Watau wannan mummunan zato nasu ne ya sanya su yin shirka da Allah da ɗagawa a bayan ƙasa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. An tsaurara matakan tsaro a sama lokacin aiko da Manzon Allah (ﷺ) da saukar masa da Alƙur’ani fiye da yadda yake kafin aiko shi, don ba wa Alƙur’ani kariya ta musamman daga duk wasu shaiɗanu waɗanda za su so shigar da maganganunsu a cikinsa da kuma ƙara bayyana martabar Manzon Allah (ﷺ) a idon duniya.

2. Aljannu masu hawa sama domin satar bayanai suna da wuraren zamansu a can kafin daga bisani a hana su zama.

3. Kafin lokacin aiko Manzon Allah (ﷺ) babu wanda ake jifa da harshen wuta sai wanda ya yi satar sauraro, to amma bayan aiko Manzon Allah (ﷺ) ana jifan duk wani shaiɗani da yake ƙoƙarin ya matsa kusa don ya sato bayanai.

4. Aljannu ba su san gaibu ba; shi ya sa ba su san manufar Ubangiji ba ta hana su satar bayanai daga sama.

5. Kyautata ladabi ga Allah wajen jingina ayyukan alheri gare shi kai-tsaye, da kuma kauce wa jingina aikin sharri gare shi, domin babu wani sharri tsantsa a cikin duk ayyukan Allah, don haka ba a dangana masa shi, duk kuwa da cewa dole ne a yi imani da cewa shi ne ya halicci komai da komai mai kyau da marar kyau.

Suratul Jinn (8-10)
وَأَنَّا لَمَسْنَا ٱلسَّمَآءَ فَوَجَدْنَٰهَا مُلِئَتْ حَرَسًا شَدِيدًا وَشُهُبًا ۝٨ وَأَنَّا كُنَّا نَقْعُدُ مِنْهَا مَقَٰعِدَ لِلسَّمْعِ ۖ فَمَن يَسْتَمِعِ ٱلْـَٰٔنَ يَجِدْ لَهُۥ شِهَابًا رَّصَدًا ۝٩
وَأَنَّا لَا نَدْرِىٓ أَشَرٌّ أُرِيدَ بِمَن فِى ٱلْأَرْضِ أَمْ أَرَادَ بِهِمْ رَبُّهُمْ رَشَدًا ۝١٠

8. “Kuma lalle mu mun nemi hawa sama, sai muka same ta an cika ta da matsanancin tsaro da taurari (masu jifa da garwashi).

9. “Lalle kuma mun zamanto a da muna hawa wasu wurare nata don yin sauraro; to duk wanda ya nemi yin sauraro a yanzu zai sama wa kansa wani tauraro wanda aka tanada (don jifan sa).

10. “Kuma lalle mu ba mu sani ba, shin wani sharri ake nufi da waɗanda ke ƙasa, ko kuwa Ubangijinsu Yana nufin su da shiriya ne?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin irin maganganun da aljannu suka gaya wa jama'arsu bayan sun saurari karatun Alƙur’ani daga bakin Manzon Allah (ﷺ), inda suka shaida wa ‘yan’uwansu aljannu cewa, lalle sun nemi su hau sama don su sato labarai kamar yadda suka saba yi a can baya, amma sai suka same ta an cika ta maƙil da mala’iku ƙarfafa masu tsaron ta daga duk wani aljani mai ƙoƙarin satar bayanai daga sama, an kuma cika ta da taurari masu jifa da harasan wuta, domin ƙona duk wanda ya matso kusa da inda zai yi satar sauraro.
Aljannu suka ci gaba da ba da labarin cewa, su a da can suna samun wuraren zama a sama don sauraron tattaunawar mala’iku su saci bayanai daga gare su sai su isar da su ga bokaye a bayan ƙasa, to yanzu abu ya canja, duk wani wanda ya yi yunƙurin yiwo sauraro daga cikin aljannu, to zai samar wa kansa wani harshen wuta wanda aka tanada domin jifan sa da shi, yana matsawa kusa kuwa za a sakar masa shi ya ƙona shi murus har lahira.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Annabi (ﷺ) yana zaune a tsakiyar wasu sahabbansa mutanen Madina, sai aka yi jifa da wani tauraro sai ya yi haske, sai Manzon Allah (ﷺ) ya tambayi waɗannan sahabban cewa: “Idan irin wannan ya faru a zamanin jahiliyya me kuka kasance kuna cewa?” Sai suka ce: “Mun kasance muna cewa, wani babban mutum zai mutu, za kuma a haifi wani babban mutum.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce musu: “Ba haka ba ne, ba a jefo tauraro don mutuwar wani ko don rayuwarsa, sai dai yayin da Ubangijinmu (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hukunta faruwar wani abu, sai mala’iku masu ɗauke da Al’arshi su yi tasbihi, sai kuma mala’ikun da suke sama mai biye da su su ma su yi tasbihi, har sai tasbihin nan nasu ya iso wannan samaniyar, sannan sai mala’ikun da suke sama ta bakwai su tambayi masu ɗauke da Al’arshi labarin abin da Ubangijinsu ya faɗa. Sai su faɗa musu, sannan mala’ikun kowace sama su tambayi na sama da su, har sai labari ya iso wannan samaniyar (ta kusa) sai aljannu su wafci labarin, sai a jefe su da tauraro mai garwashi. Duk kuma abin da suka zo da shi yadda yake gaskiya ne, sai dai suna ƙare-ƙare a cikinsa.” [Ahmad #1882 da Tirmizi #3503].

Sai aljannu suka ci gaba da bayanin cewa, su ba su san dalilin da ya kawo wannan matakin tsaro mai tsanani haka ba; shin ana nufin wani sharri ne ga waɗanda suke rayuwa a bayan ƙasa a duniya, ko kuma dai Allah ya yi nufin su da wani alheri ne? Domin ga shi dai labarai sun daina zuwa daga sama, watau dai babu makawa akwai ɗaya daga cikin abubuwan nan guda biyu da ya faru, amma su ba su san wane ne dalilin ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Aljannu su ma kamar mutane suke, cikinsu akwai nagari akwai kafirai da fasiƙai; su ma kuma ƙungiyoyi ne daban-daban, akwai masu bin gaskiya akwai kuma karkatattu masu bin ƙarya da masu aikata bidi’o’i daban-daban.

2. Girman Ƙudurar Allah da cikar ikonsa, don haka babu mai gagarar sa ko ya kuɓuce wa kamunsa.

3. Alƙur’ani dukansa shiriya ne, duk wanda ya saki Alƙur’ani to ya kama hanyar ɓata.

4. Babu laifi mutum ya riƙa ambaton ni’imar da Allah ya yi masa don godiya gare shi.

5. Cikar adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da kamalar falalarsa ga bayinsa.

6. Duk wanda zai karkace wa hanyar Allah, to ya kama hanyar shiga wuta.

7. Tsayuwa a kan Musulunci da aiki da shi shi ne hanyar samun alherin duniya da lahira.

8. Tsoratar da mushirikan Makka da cewa, idan har suka ƙi bin hanyar Musulunci suka ci gaba da kafiricinsu, to za su gamu da fari da yunwa saboda rashin ruwa da zai same su. Wannan narkon kuwa ya faru da su bayan hijirar Manzon Allah (ﷺ) lokacin da ya roƙi Allah ya kama su da fari irin wanda ya jarrabi mutanen Annabi Yusuf da shi.

Suratul Jinn (11-17)
وَأَنَّا مِنَّا ٱلصَّٰلِحُونَ وَمِنَّا دُونَ ذَٰلِكَۖ كُنَّا طَرَآئِقَ قِدَدٗا ١١ وَأَنَّا ظَنَنَّآ أَن لَّن نُّعۡجِزَ ٱللَّهَ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَن نُّعۡجِزَهُۥ هَرَبًا ١٢ وَأَنَّا لَمَّا سَمِعۡنَا ٱلۡهُدَىٰٓ ءَامَنَّا بِهِۦۖ فَمَن يُؤۡمِنۢ بِرَبِّهِۦ فَلَا يَخَافُ بَخۡسٗا وَلَا رَهَقٗا ١٣ وَأَنَّا مِنَّا ٱلۡمُسۡلِمُونَ وَمِنَّا ٱلۡقَٰسِطُونَۖ فَمَنۡ أَسۡلَمَ فَأُوْلَٰٓئِكَ تَحَرَّوۡاْ رَشَدٗا ١٤ وَأَمَّا ٱلۡقَٰسِطُونَ فَكَانُواْ لِجَهَنَّمَ حَطَبٗا ١٥ وَأَلَّوِ ٱسۡتَقَٰمُواْ عَلَى ٱلطَّرِيقَةِ لَأَسۡقَيۡنَٰهُم مَّآءً غَدَقٗا ١٦ لِّنَفۡتِنَهُمۡ فِيهِۚ وَمَن يُعۡرِضۡ عَن ذِكۡرِ رَبِّهِۦ يَسۡلُكۡهُ عَذَابٗا صَعَدٗا ١٧

11. “Lalle daga cikinmu akwai salihai, daga cikinmu kuma akwai waɗanda ba haka suke ba; mun zamanto hanyoyi daban-daban.

12. “Kuma lalle mu mun tabbatar cewa ba za mu gagari Allah ba a bayan ƙasa, ba kuma za mu gagare Shi ba a guje.

13. “Lalle kuma mu lokacin da muka ji Alƙur’ani, sai muka yi imani da shi, to duk wanda zai yi imani da Ubangijinsa, to zai tsoron ƙwara ko zalunci ba.

14. “Kuma lalle mu a cikinmu akwai Musulmi, a cikinmu kuma akwai karkatattu; saboda haka duk wanda ya musulunta, to waɗannan sun nufi hanyar shiriya.

15. “Amma kuma karkatattu, to sun kasance makamashi ne ga (wutar) Jahannama.”

16. Da kuwa (mutan Makka) sun daidaita a kan (Musulunci), to lalle da Mun shayar da su ruwa mai yawa.

17. Don Mu jarrabe su game da shi. Duk kuwa wanda ya kau da kai daga ambaton Ubangijinsa to zai saka shi cikin azaba mai wahala.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ci gaba da ba da labarin maganganun aljannu ga jama’arsu, inda suka ci gaba da sanar da su cewa, lalle su aljannu a cikinsu akwai salihai masu tsoron Allah akwai kuma kafirai da fasiƙai a cikinsu, sun zamanto ƙungiyoyi daban-daban masu mabambanta ra’ayoyi da soye-soyen zuciya.
Suka kuma tabbatar da cewa, su sun san ba za su gagari Allah a bayan ƙasa ba idan ya so kama su da wani al’amari, hakanan babu inda za su iya guduwa su tsere masa, domin ikonsa a kewaye yake da su ta kowane ɓari.

Sai kuma suka bayyana cewa, su tun lokacin da suka ji karatun Alƙur'ani suka kuma ji yana kiran su zuwa ga shiriya sai suka yi imani da shi, kuma sun tabbata duk wanda ya yi imani da Ubangijinsa Allah, ba zai ji tsoron a tauye masa ladansa ba kuma ba zai yi fargabar za a ƙara masa wani laifin da bai aikata ba a kan laifukansa. Watau dai sun sakankance da adalcin Ubangiji da alherin da yake kiran su zuwa gare shi ba tare da wata cutuwa ba.
Sai suka sake bayyana kasha-kashensu da sakamakon kowane kashi, inda suka tabbatar da cewa, a cikinsu akwai Musulmai masu bin Allah sau-da-ƙafa akwai kuma karkatattu waɗanda suka saki hanyar Allah da gaskiya, don haka duk wanda ya musulunta ya miƙa wuya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to waɗannan su ne suka nufi hanyar shiriya da gaskiya, watau sun kama hanyar zuwa Aljanna.
Amma karkatattu masu sakin hanyar gaskiya, to waɗannan su ne za su kasance makamashin wutar Jahannama da za a riƙa rura ta da su da ire-irensu daga cikin mutane.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi wa Manzonsa wahayi cewa, da mutane da aljannu za su daidaita a kan hanyar Musulunci su ƙanƙame wa koyarwarsa, to da zai shayar da su ruwa mai yawa, ya ƙara musu ni'imomi masu ɗimbin yawa, domin ya jarrabe su da su, don bayyana waɗanda za su gode masa da waɗanda za su yi masa butulci daga cikinsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya tsoratar da su cewa, duk wanda ya bijire wa Alƙur'ani da wa'azuzzukan da ke cikinsa, to ya sani Ubangijinsa Allah zai shigar da shi wata azaba mai wahalar da ba zai iya jure mata ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Masallaci ɗakin Allah ne, kuma ana gina shi ne domin bautar Allah shi kaɗai a cikinsa.

2. Duk wata ibada haƙƙin Allah ce shi kaɗai, bai halatta a karkatar da ita ga waninsa ba.

3. Manzon Allah (ﷺ) bawan Allah ne, kuma babu wani kirari da za a yi masa kamar a ce masa bawan Allah Manzonsa.

4. Tsananin tasirin da Alƙur'ani ya yi wa aljannu yayin da suke sauraron karatunsa, har sai da ta kai kamar su danne Manzon Allah (ﷺ), yayin da suka yi masa cincirindo wasu kan wasu don tsananin son su ji karatunsa.

5. An umarci Annabi (ﷺ) ne da ya shelanta Kaɗaitakar Allah wajen bautarsa da kaɗaitakar siffofinsa da ayyukansa da kore bautar wani ba Allah ba.

6. Allah ne kaɗai mai cutarwa ko amfanarwa, babu wanda zai iya yi wa wani abin da Allah bai yi masa ba.

7. Annabi (ﷺ) bawan Allah ne ba ya cutarwa ko amfanarwa ba tare da izinin Allah ba.

8. Martani a kan masu riƙe mala'iku ko annabawa ko salihai, suna zaton za su iya yi musu abin da Allah bai yi musu ba, ko su riƙe su iyayen giji ba Allah ba.

9. Aikin Manzon Allah (ﷺ) shi ne isar da saƙon Allah ga mutane da aljannu, don haka duk wani alheri ya tattara cikin yi masa biyayya da riƙo da sunnarsa.

10. Babu mai iya kare wa wani abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nufe shi da shi ko da duk halittun duniya za su haɗu a kan haka.

11. Babu wata mafaka ko matsera daga Allah sai dai zuwa gare shi.

12. Duk wanda ya saɓa wa Manzon Allah (ﷺ) ta hanyar shirka ko kafirci ko ƙaryata shi, to zai dawwama ne a cikin wutar Jahannama babu mai fitar da shi har abada.

13. Ranar alƙiyama rana ce da kowa zai gane haƙiƙanin gaskiyar da ake faɗa masa a duniya.

Suratul Jinn (18-24)

وَأَنَّ ٱلۡمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدۡعُواْ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدٗا ١٨ وَأَنَّهُۥ لَمَّا قَامَ عَبۡدُ ٱللَّهِ يَدۡعُوهُ كَادُواْ يَكُونُونَ عَلَيۡهِ لِبَدٗا ١٩ قُلۡ إِنَّمَآ أَدۡعُواْ رَبِّي وَلَآ أُشۡرِكُ بِهِۦٓ أَحَدٗا ٢٠ قُلۡ إِنِّي لَآ أَمۡلِكُ لَكُمۡ ضَرّٗا وَلَا رَشَدٗا ٢١ قُلۡ إِنِّي لَن يُجِيرَنِي مِنَ ٱللَّهِ أَحَدٞ وَلَنۡ أَجِدَ مِن دُونِهِۦ مُلۡتَحَدًا ٢٢ إِلَّا بَلَٰغٗا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِسَٰلَٰتِهِۦۚ وَمَن يَعۡصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَإِنَّ لَهُۥ نَارَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ٢٣ حَتَّىٰٓ إِذَا رَأَوۡاْ مَا يُوعَدُونَ فَسَيَعۡلَمُونَ مَنۡ أَضۡعَفُ نَاصِرٗا وَأَقَلُّ عَدَدٗا ٢٤

18. Kuma lalle masallatai na Allah ne, saboda haka kada ku bauta wa wani tare da Allah.

19. Kuma lalle yadda lamarin yake, yayin da Bawan Allah (Annabi Muhammadu) ya tashi yana bauta masa, sai (aljannu) suka kusa su zamo wasu kan wasu don cincirindo a kansa.

20. Ka ce: “Lalle ina bauta wa Ubangijina ne kawai, ba kuwa na tara wani da Shi.”

21. Kuma ka ce: “Lalle ni ban mallaki kare muku wata cuta ko janyo muku wani alhairi ba.”

22. Ka ce: “Lalle ni ba wani mai kare ni daga (azabar) Allah, kuma ba zan taɓa samun wata mafaka in ba tasa ba.

23. “Sai dai isar da aike daga Allah da kuma saƙwanninsa. Duk kuwa waɗanda suka saɓa wa Allah da Manzonsa, to lalle suna da wutar Jahannama, suna madawwama a cikinta har abada.”

24. Har yayin da (kafirai) suka ga abin da ake yi musu alƙawari da shi, to ba da daɗewa ba za su san wa ya fi raunanan mataimaka da kuma ƙanƙantar jama’a.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, daga cikin abubuwan da ya yi wa Manzonsa (ﷺ) wahayi da su akwai cewa, lalle masallatai nasa ne, domin bautar sa shi kaɗai, don haka kada su sake kiran wasu da sunan bauta a cikinsu har abada, domin idan sun yi haka sun zama kamar Yahudu da Nasara a wuraren bautarsu inda suke bautar wasu annabawa da salihai tare da Allah a cikinsu.

An karɓo daga Ummu Habiba da Ummu Salama , sun ba wa Manzon Allah (ﷺ) labarin wata coci da suka gano a Habasha mai cike da hotuna. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Waɗannan mutane sun kasance idan mutumin kirki ya mutu a cikinsu sai su gina masallaci a kan ƙabarinsa, su zana irin waɗannan hotunan. Waɗannan su ne ashararan halitta a wurin Allah Ta’ala a ranar alƙiyama.” [Bukhari #427 da Muslim #528].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lokacin da bawansa Annabi Muhammadu (ﷺ) yake tsaye a *Baɗnu Nakhla* yana bauta masa aljannu sun kusa su zamo wasu kan wasu a wurinsa saboda tsananin cinkoso yayin da suke sauraron karatun Alƙur’ani da yake yi.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya bayyana wa mushirikai tsantsar abin da yake kiran su a kansa, da cewa, lalle shi Ubangijinsa kaɗai yake bauta wa, kuma ba zai yarda ya haɗa wani da bautar sa ba kowane ne. Ya kuma sanar da su cewa, shi ba zai iya kare su daga wata cuta da Allah ya ƙaddara musu ba, ba kuma zai iya janyo musu wani amfani da Allah ya hana musu ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya bayyana musu cewa, shi a karan-kansa ba mai iya kare kansa ba ne, ballantana ya kare wani daga azabar Allah, domin babu mai iya tserar da shi daga kamun Allah idan ya saba masa ya ƙi bin umarninsa, ba kuma zai taba samun wata mafaka in ba tasa ba. Ya sanar da su cewa, abin da kawai ya mallaka shi ne ya isar musu da saƙon da Allah ya umarce shi ya isar musu da manzancin da ya aiko shi da shi zuwa gare su, don hujjar Allah ta tsaya a kansu da sauran mutane. Don haka duk wanda ya saba wa Allah da Manzonsa, to makomarsa ita ce wutar Jahannama da za a jefa shi a cikinta ya dawwama ba zai taba fitowa daga cikinta ba har abada.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Manzonsa (ﷺ) cewa, duk da wannan gargaɗi da yake yi wa kafirai, ba fa za su bar kafircinsu ba har sai yayin da a ranar alƙiyama suka ga dahir, watau azabar da ake yi musu alƙawarin zuwanta a duniya, to a lokacin ne za su san wane ne ya fi raunanan mataimaka ya kuma fi ƙarancin jama'a masu kawo masa ɗauki.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu wanda ya san ranar tashin alƙiyama sai Allah shi kaɗai.

2. Duk da kasancewar alƙiyama ta kusanto, to amma babu wanda ya san gwargwadon kusantowarta sai Allah shi kaɗai.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai ne masanin gaibi kowane iri.

4. Idan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ga dama yakan tsinkayar da wani abu na gaibinsa ga wani manzo daga cikin manzanninsa, domin ya zamanto mu'ujiza a gare shi.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya tsaro na mala'iku a gaban Manzonsa (ﷺ) da bayansa don ba wa wahayi kariya daga shaiɗanu, don haka ba za su iya satar wani abu daga cikinsa ba, ba kuma za su iya ƙarawa ko su rage ba.

6. Shaidar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga manzanninsa cewa, sun isar da saƙwanninsa da ya aiko su da su.

7. Faffaɗan ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wanda ya kewaye komai.

Suratul Jinn (25-28)
قُلۡ إِنۡ أَدۡرِيٓ أَقَرِيبٞ مَّا تُوعَدُونَ أَمۡ يَجۡعَلُ لَهُۥ رَبِّيٓ أَمَدًا ٢٥ عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ فَلَا يُظۡهِرُ عَلَىٰ غَيۡبِهِۦٓ أَحَدًا ٢٦ إِلَّا مَنِ ٱرۡتَضَىٰ مِن رَّسُولٖ فَإِنَّهُۥ يَسۡلُكُ مِنۢ بَيۡنِ يَدَيۡهِ وَمِنۡ خَلۡفِهِۦ رَصَدٗا ٢٧ لِّيَعۡلَمَ أَن قَدۡ أَبۡلَغُواْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّهِمۡ وَأَحَاطَ بِمَا لَدَيۡهِمۡ وَأَحۡصَىٰ كُلَّ شَيۡءٍ عَدَدَۢا ٢٨

25. Ka ce: "Ni ban sani ba, shin kusa yake abin da ake yi muku alƙawarinsa ko kuwa Ubangijina zai sanya masa zamani mai tsawo?"

26. "(Shi ne) Masanin gaibu, sannan ba Ya bayyana gaibunsa ga wani.

27. “Sai manzo da ya yarda da shi, shi kuma lalle Yakan sanya masa tsaro ta gabansa da ta bayansa.

28. “Don Ya bayyanar da cewa, haƙiƙa sun isar da saƙwannin Ubangijinsu, Ya kuma kewaye da (sanin) abin da yake tare da su, Ya kuma ƙididdige adadin kowane abu.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya amsa wa kafirai tambayar izgili da suke damun sa da ita na cewa, sai ya faɗa musu yaushe ne alƙiyama za ta zo? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi ya bayyana musu cewa, shi ba shi da masaniya ga abin da ake yi musu alƙawarin zuwansa na alƙiyama ko na azaba, kusa yake ko kuma Ubangijinsa zai sanya masa wani lokaci mai tsawo da ba wanda ya san shi sai shi (Mai tsarki da ɗaukaka)? Domin shi ne masanin gaibu gaba ɗaya, kuma ba ya bayyana wa wani mahaluƙi gaibinsa, shi kaɗai ne ya keɓanta da saninsa, sai dai kuma yakan sanar da wani manzo da ya zaɓa abin da ya ga dama ya sanar da shi gwargwadon hikimarsa, domin ya zamanto mu’ujiza a gare shi. Yana kuma aiko da mala’iku ga wannan Manzon ta gabansa da bayansa suna tsaron sa don kada shaiɗanu su sami kusantar sa har su ƙara wani abu ko su rage daga cikin wahayin da yake yi masa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi haka ne don ya tabbatar da cewa, manzanninsa sun isar da saƙwannin Ubangijinsu ba daɗi ba ragi. Allah kuwa ya kewaye da sanin duk abin da yake tare da su ya kuma ƙididdige adadin komai, domin babu abin da yake ɓuya gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar *Kiyamul Laili*, watau sallar dare, domin ita ce sallar nafilar da ta fi kowacce lada, domin Annabi (ﷺ) yana cewa: “Mafi falalar salla bayan sallar farilla ita ce sallar cikin dare.” [Muslim 1163].

2. Shari’a ba ta yi umarni da tsayuwar dare gaba ɗayansa ba, domin dare lokaci ne na hutu da barci da sauran haƙƙoƙin jiki da na iyali. Annabi (ﷺ) yana cewa: “Amma ni ina salla ina kuma yin barci.... Wanda duk ya ƙyamaci sunnata, to ba ya tare da ni.” [Bukhari #5063 da Muslim #1401].

3. Umarni da karatun Alƙur’ani cikin nutsuwa a sallar dare, domin yin haka abu ne mai kyau.

4. Alƙur’ani ya ƙunshi abubuwa masu nauyin gaske, waɗanda suka haɗa da farillai da hukunce-hukunce da ladubba da suke buƙatar danne zuciya da yaƙi da shaiɗanu domin riƙo da su. Alƙur’ani kuma yana da nauyi wajen saukar da shi ga Manzon Allah (ﷺ), sannan isar da shi ga mutane da kiran su zuwa ga aiki da dokokinsa shi ma abu ne mai matuƙar nauyi da wahala.

5. Duk wani mai kira zuwa ga Allah yana buƙatar guzuri na ƙarfafa alaƙarsa da Mahaliccinsa Allah, domin samun tallafi da ɗauki a kan aikin da yake gabansa na jan hankalin mutane da wa’azantar da su. Babu wata hanya ta ƙarfafa alaƙar bawa da Ubangijinsa kamar ibada, a cikin ibadu kuma babu kamar salla.

6. Samun nutsuwar zuciya da daddare yana da matuƙar tasiri wajen fahimtar Alƙur’ani da haddarsa.

7. Ana son karatun Alƙur’ani cikin nutsuwa kuma daki-daki, tare da bai wa kowane harafi haƙƙinsa, watau abin da ake kira ilimin *Tajwidi*.

8. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kwaɗaitar da Manzonsa (ﷺ) a kan tsayuwar dare saboda da rana yana da ayyuka masu yawa da ba za su ba shi damar yin sauran sallolin nafila ba, domin yakan shagaltu da kiran mutane zuwa ga Allah da koyar da sahabbansa Alƙur’ani da hukunce-hukuncen addini da

tattaunawa da mushirikai da ɗawainiya da raunana. Duka waɗannan al’amura su ne Allah ya kira da 'ayyuka masu yawa'.

9. Umarni ga Manzon Allah (ﷺ) da ya yi watsi da duk wani al’amari da zai ɗauke masa hankali game da tsayuwar dare da ayyukansa na rana masu alaƙa da yaɗa addinin Allah da koyar da al’umma. Duk wani aiki na Manzon Allah (ﷺ) yana da alaƙa da addinin Allah, har cinsa da shansa da barcinsa da hulɗarsa da matansa da ‘ya‘yansa, duk waɗanan sun jiɓinci bautar Allah. Don haka a nan ba a umarce shi ya yi watsi da sauran al’amuran rayuwa ba ne, watau ‘Ruhbaniyanci’ da bijire wa mata da jin daɗin duniya da Allah ya halatta wa bayinsa muminai.

73-Suratul Muzzammil

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Muzzammil*'. Kalmar *Al-Muzzammil* tana nufin wanda ya lulluɓa da mayafi. Ana nufin Manzon Allah (ﷺ).

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai sun bayyana cewa, Sura ce *Makkiyya* sai dai ayar ƙarshe ita ce *Madaniyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta uku (3) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Muddassir*', gabanin '*Suratul Ƙalam'.*

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin ne (20). Amma a lissafin mutanen Basra goma sha tara ne (19), a lissafin mutanen Madina kuwa goma sha takwas (18) ne.

5. Babban Jigonta:
Tana karantar da cewa, duk wanda zai tashi domin kira zuwa ga Allah, to yana buƙatar ƙarfafa alaƙarsa da Allah domin tunkarar wahalhalun da zai gamu da su.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Umartar Annabi (ﷺ) da tsaiwar dare da yabon masu tsaiwar dare.
• Karfafa gwiwar Manzon Allah (ﷺ) game da ɗaukar nauyin wahayin Allah (ﷺ) da isar da shi ga al'ummarsa.
• Umartar Manzon Allah (ﷺ) da ya kau da kansa daga mushirikai masu ƙaryata shi.
• Tsoratar da kafirai azabar ranar lahira da yi musu kashedi da gamuwa da irin uƙubar da ta auka wa Fir'auna da mutanensa yayin da suka ƙaryata Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
• Shafe hukuncin wajabcin tsayuwar dare da kwaɗaitarwa a kan tsayuwar wani ɓangare na dare, domin la'akari da masu uzuri na yau da gobe.
• Alƙawarin babban sakamako ga masu aikata alheri.
• Umarni da gaggauta tuba zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Muzzammil (1-9)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلۡمُزَّمِّلُ ۝١ قُمِ ٱلَّيۡلَ إِلَّا قَلِيلٗا ۝٢ نِّصۡفَهُۥٓ أَوِ ٱنقُصۡ مِنۡهُ قَلِيلًا ۝٣ أَوۡ زِدۡ عَلَيۡهِ وَرَتِّلِ ٱلۡقُرۡءَانَ تَرۡتِيلًا ۝٤ إِنَّا سَنُلۡقِي عَلَيۡكَ قَوۡلٗا ثَقِيلًا ۝٥ إِنَّ نَاشِئَةَ ٱلَّيۡلِ هِيَ أَشَدُّ وَطۡا وَأَقۡوَمُ قِيلٗا ۝٦ إِنَّ لَكَ فِي ٱلنَّهَارِ سَبۡحٗا طَوِيلٗا ۝٧ وَٱذۡكُرِ ٱسۡمَ رَبِّكَ وَتَبَتَّلۡ إِلَيۡهِ تَبۡتِيلًا ۝٨ رَّبُّ ٱلۡمَشۡرِقِ وَٱلۡمَغۡرِبِ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱتَّخِذۡهُ وَكِيلٗا ۝٩

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya kai wannan mai lulluɓa!

2. Ka yi tsaiwar dare sai ɗan kaɗan (daga cikinsa).

3. Rabinsa ko kuma ka rage kaɗan daga gare shi.

4. Ko ka ƙara a kansa, ka kuma karanta Alƙur'ani daki-daki.

5. Lalle Mu da sannu za Mu saukar maka da zance mai nauyi.

6. Lalle tsayuwar dare ita ta fi tsananin dacewa (game da nutsuwa), ta kuma fi daidaitar magana.

7. Lalle da rana kana da harkoki masu yawa.

8. Ka kuma ambaci sunan Ubangijinka kuma ka yanke alaƙarka da komai don bautarsa.

9. (Shi ne) Ubangijin mahudar rana da mafaɗar rana, babu wani abin bauta wa da gaskiya sai Shi, saboda haka ka riƙe Shi Abin dogara.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da kiran Manzonsa (ﷺ) da sunan wanda yake lulluɓe da tufafinsa, ya umarce shi ya tashi cikin dare ya yi salla kada ya rage komai daga cikin darensa sai ɗan kaɗan. Ko kuma ya sallaci rabin daren idan yana so, ko ya sallaci ƙasa da rabi har ya koma sulusi, watau kashi ɗaya bisa uku, ko kuma idan ya ga dama ya ƙara har ya kai kashi biyu bisa uku, watau dai gwargwadon buƙatarsa da ƙoƙarinsa.

An karɓo daga A'isha (Allah ya kara mata yarda), ta ce: Annabi (ﷺ) ya zamanto baccinsa kaɗan ne bayan da aka saukar masa faɗar Allah: "Ka raya dare sai ɗan kaɗan daga cikinsa." [Nasa'i, *Al-Kubra* #11564 da Abu Ya'ala #4939].

Sannan Allah ya umarce shi da ya karanta Alƙur'ani cikin nutsuwa daki-daki, don ya sami tuntuntuni a kansa yadda ya kamata.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "A ranar alƙiyama za a ce wa makarancin Alƙur'ani: "Karanta shi ka ƙara ɗaukaka, karanta shi a natse daki-daki kamar yadda kake karanta shi a natse daki-daki a duniya, domin matsayinka yana kan ƙarshen ayar da za ka karanta." [Ahmad #6799 da Abu Dawud #1464 da Tirmizi #3141, 3142].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi wa Manzonsa (ﷺ) wannan umarni ne, don ya shirya sosai, domin lalle zai sauko masa da zance mai nauyi, watau Alƙur'ani da zai yiwo masa wahayinsa.

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Al-Harisu ɗan Hisham ya tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa: "Yaya wahayi yake zuwa maka?" Sai ya ce: "Wani lokaci yana zuwa mini kamar ƙarar ƙaraurawa, shi ne mafi tsanani a gare ni har zuwa lokacin da zai gushe mini bayan na kiyaye abin da Mala'ika Jibrilu ya faɗa min. A wani lokaci kuwa, Mala'ika Jibrilu yakan fito mini a surar mutum ya yi magana da ni, sai in kiyaye duk abin da ya faɗa mini." A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Tabbas na gan shi ana yi masa wahayi a lokaci mai tsananin sanyi, amma ana gama yi masa wahayi sai ka ga goshinsa yana tsattsafo da gumi. [Bukhari #2].

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: "Annabi (ﷺ) ya kasance idan ana yi masa wahayi yana kan taguwarsa, takan yi ƙasa da ƙirjinta har ta kasa motsawa." Sai ta karanta wannan ayar. [Al-Hakim #3865 da Musnad #24868].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) hikimar sallar dare da cewa, ta fi dacewa da nutsuwar zuciya da taimakawa wajen fahimtar zance daidai, domin da zuciya da harshe za su haɗu a kan abin da mutum yake karantawa, sai ya fi saurin fahimtar sa, domin rashin samun abin da zai ɗauke masa hankali a lokacin.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, da rana kuwa yana da ayyuka masu yawa da za su hana shi shagaltuwa da sallolin nafila, don haka sai ya ribaci dare ya yi ta salla a cikinsa. Ya kuma umarce shi da ambaton sa da kowane irin nau'in zikiri, kuma ya watsar da komai ya duƙufa wajen bauta masa da tsantsanta bautarsa gare shi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, shi ne Ubangijin mahudar rana da mafaɗarta, kuma babu wani abin bauta da gaskiya sai shi, don haka ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya riƙe shi abin dogaro a cikin dukkan al'amuransa na rayuwa da na addini.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umartar Manzon Allah (ﷺ) da yin haƙuri da kawar da kai daga masu ƙaryata shi, watau kada ya ɗauki wani mataki na ramuwa a kan abin da suke yi masa, domin a wannan lokaci Musulmi raunana ne ba su da ƙarfin da za su tunkari Ƙuraishawa da sauran al'ummar Larabawa. Don haka duk sanda Musulmi suke cikin rauni to wajibi ne su yi taka-tsantsan, su kawar da kai daga masu muzguna musu.

2. Kyakkyawar ƙauracewa ita ce wadda babu cutarwa ga wanda aka ƙaurace wa da fatar baki ko a aikace, ba tare kuma da ɗaukar matakin ramuwar gayya ba.

3. A aya ta [10] akwai kyakkyawar tarbiyya ga duk wani Musulmi, inda Allah ya haɗa masa abin da zai buƙata don zama da mutune a cikin kalmomi biyu: Ko dai ya zama mai cakuɗuwa da mutane ne, to wannan dole sai ya yi haƙuri game da cutarwarsu gare shi, saboda matuƙar zai sa wa zuciyarsa cewa, ba zai ji ko ya ga wani mummuna daga wajensu ba, to zai zama cikin damuwa koyaushe. Idan kuwa zai bar cakuɗa da su ne, to sai ya yi kyakkyawar ƙauracewa, watau ba tare da aikata abin da zai cutar da wani ba.

4. Azabar lahira ta ƙunshi dangogin azaba daban-daban.

5. Yawancin 'yan-tamore a duniya, su ne masu ƙaryata gaskiya yayin da ta zo musu.

6. Sharholiya da tarin dukiya suna hana bin hanyar Allah.

7. Rikirkicewar tsarin gudanar da ƙasa da sama a ranar alƙiyama.

8. Aiko da manzanni yana daga cikin sunnar Allah, don yanke hanzari da kafa hujja.

9. Manzannin Allah za su zama masu ba da shaida a gaban Allah a kan al'ummunsu a ranar alƙiyama, inda za su tabbatar da cewa, sun isar musu da saƙon Allah, wasu suka yi imani wasu kuma suka ƙaryata.

10. Kamanceceniya tsakanin manzancin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da manzancin Annabi (ﷺ), domin da mutanen Makka da na Misra duk sun yi tarayya wajen bautar wanin Allah da kuma rena manzonsu, don ganin shi mutum ne kamarsu.

11. Tsananin firgita da razani a ranar lahira wanda zai sanya yaro ƙarami furfura. Don haka ya wajaba ga duk wani mai hankali ya yi masa kyakkyawan tanadi tun daga duniya, kada ya yi sake dogon buri ya ɗauke masa hankali ya yi watsi da aiki na ƙwarai har mutuwa ta zo ta ɗauke shi.

Suratul Muzzammil (10-18)

وَٱصۡبِرۡ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَٱهۡجُرۡهُمۡ هَجۡرٗا جَمِيلٗا ١٠ وَذَرۡنِي وَٱلۡمُكَذِّبِينَ أُوْلِي ٱلنَّعۡمَةِ وَمَهِّلۡهُمۡ قَلِيلًا ١١ إِنَّ لَدَيۡنَآ أَنكَالٗا وَجَحِيمٗا ١٢ وَطَعَامٗا ذَا
غُصَّةٖ وَعَذَابًا أَلِيمٗا ١٣ يَوۡمَ تَرۡجُفُ ٱلۡأَرۡضُ وَٱلۡجِبَالُ وَكَانَتِ ٱلۡجِبَالُ كَثِيبٗا مَّهِيلًا ١٤ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَآ إِلَيۡكُمۡ رَسُولٗا شَٰهِدًا عَلَيۡكُمۡ كَمَآ أَرۡسَلۡنَآ
إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ رَسُولٗا ١٥ فَعَصَىٰ فِرۡعَوۡنُ ٱلرَّسُولَ فَأَخَذۡنَٰهُ أَخۡذٗا وَبِيلٗا ١٦ فَكَيۡفَ تَتَّقُونَ إِن كَفَرۡتُمۡ يَوۡمٗا يَجۡعَلُ ٱلۡوِلۡدَٰنَ شِيبًا ١٧ ٱلسَّمَآءُ مُنفَطِرُۢ
بِهِۦۚ كَانَ وَعۡدُهُۥ مَفۡعُولًا ١٨

10. Kuma ka yi haƙuri a kan abin da suke faɗa, kuma ka ƙaurace musu kyakkyawar ƙauracewa.

11. Ka kuma bar ni da masu ƙaryatawa ma'abota ni'ima, ka kuma ɗan saurara musu.

12. Lalle a wurinmu akwai maruruwa da kuma (wutar) Jahimu.

13. Da kuma abinci mai shaƙewa da kuma azaba mai raɗaɗi.

14. A ranar da ƙasa da duwatsu za su girgiza, duwatsun kuma su kasance rairayi tilis.

15. Lalle Mu Muka aiko muku da Manzo yana mai shaida a kanku kamar yadda Muka aiko wani manzo zuwa ga Fir'auna.

16. Sai Fir'auna ya saɓa wa Manzon, sai Muka kama shi kamu mai tsanani.

17. Ta yaya idan kuka kafirta za ku iya kare kanku daga ranar da za ta mayar da yara ƙanana su zama masu furfura?

18. Sama za ta kece saboda ita (ranar). Alƙawarinsa ya kasance abin aikatawa ne.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya yi haƙuri game da maganganun izgili da cin fuska da yake ji daga mushirikai masu ƙaryata shi, ya ci gaba da da'awarsa zuwa ga Allah, kada ya daka ta waɗanda suke so su hana ruwansa gudu, ya kuma ƙaurace musu kyakkyawar ƙauracewa wadda babu cutarwa a cikinta.

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da kada ya damu da al'amarin masu ƙaryata shi, 'yan tamore kawai a rayuwar duniya, ya bar shi ya ga yadda zai yi da su, ya kuma saurara musu kaɗan har lokacin zuwan ajalinsu inda ido zai raina fata.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da kafirai tsananin azabarsa ta lahira, ya tabbatar musu cewa, ya yi tanadin maruruwa masu nauyi da wuta mai tsananin ruruwa. Abincinsu ma irin mai shaƙe maƙoshi ne saboda tsananin ɗacinsa da warinsa, ga kuma wuta mai tsananin zafi da ƙuna.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan azaba za ta sami waɗannan masu ƙaryatawar ne a ranar da ƙasa da duwatsu za su girgiza, duwatsu kuma su zama rairayi tilis, saboda tsananin tsoro na wannan ranar.

kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da waɗannan ‘yan tamore da azabar duniya irin wadda ta auka wa kafirai irinsu a baya da cewa, ya aiko musu da manzo don ya zama mai ba da shaida a kan ayyukansu a ranar alƙiyama kamar yadda ya aika wa Firʾauna Manzo shi ne Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), to amma sai Firʾauna ya saɓa wa wannan Manzon ya ƙaryata shi, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa matsanancin kamu, watau ya nutsar da shi har da jamaʾarsa cikin kogin Maliya, suka hallaka baki ɗaya; azabar lahira kuma tana nan tana jiran su. Don haka su ma mutanen Makka su guji saɓa wa Manzonsu, in ba haka ba, kuma irin abin da ya sami Firʾauna da mutanensa ya same su.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake tsoratar da su azabar lahira yana tsawatar musu da cewa, ta yaya za su iya kare kansu daga azabar wata rana mai tsawo da tsananin gaske, mai mayar da yara ƙanana su zama masu furfura, saboda tsananin firgicin da ke cikinta da ababen ban tsoro da ta ƙunsa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, saboda tashin hankalin da ke cikin wannan rana sama za ta tsattsage, duk abubuwan da suke cikinta su tarwatse. Wannan kuma alƙawarin Allah ne, alƙawarinsa kuwa abin aikatawa ne babu kokwanto.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaddara ayyukan bayinsa, ya kuma hore musu damar aikata duk abin da suka so aikatawa; mai kyau ko marar kyau.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya san ayyukan da bayinsa suka gabatar da ma waɗanda ba su gabatar ba.

3. Umarnin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake yi wa Manzonsa (ﷺ) umarni ne ga alʾummarsa, sai abin da dalili ya togace wanda ya zama *'khususiyya*' ga Annabi (ﷺ) shi kaɗai.

4. Shafe wajabcin tsayuwar dare da kwaɗaitarwa a kan sallatar abin da ya sauwaƙa.

5. Dukkan ayyukan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) suna tattare da hikima.

6. Duk wani tsanani yakan jawo sauƙi a shariʾar Musulunci.

7. Rashin lafiya da halin tafiya, uzururruka ne da sukan jawo wa bayi sassauci.

8. Falalar fita fatauci don neman arziki, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya keɓance shi da ambato ya kuma haɗa shi da fita jihadi don ɗaukaka kalmarsa.

9. Kasuwanci yana daga cikin mafiya kyan hanyoyin neman arziki.

10. Mafi girman ibadu bayan Tauhidi su ne sallolin farilla da fitar da zakka; ta farko kyautatawa ce tsakanin bawa da mahaliccinsa, ta biyu kuwa kyautatawa ce tsakanin bayi a junansu.

11. Falalar Allah da yalwar rahamarsa, don haka ya yi wa duk wanda ya aikata alheri alƙawarin sakamako fiye da abin da ya aikata.

12. Duk yawan aikin alherin bawa da yawan ibadarsa yana buƙatar yawaita neman gafarar Allah, domin ya yafe masa gajiyawarsa da kasawarsa.

Suratul Muzzammil (19-20)

إِنَّ هَٰذِهِۦ تَذۡكِرَةٞۖ فَمَن شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلًا ١٩ ۞إِنَّ رَبَّكَ يَعۡلَمُ أَنَّكَ تَقُومُ أَدۡنَىٰ مِن ثُلُثَيِ ٱلَّيۡلِ وَنِصۡفَهُۥ وَثُلُثَهُۥ وَطَآئِفَةٞ مِّنَ ٱلَّذِينَ مَعَكَۚ وَٱللَّهُ يُقَدِّرُ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَۚ عَلِمَ أَن لَّن تُحۡصُوهُ فَتَابَ عَلَيۡكُمۡۖ فَٱقۡرَءُواْ مَا تَيَسَّرَ مِنَ ٱلۡقُرۡءَانِۚ عَلِمَ أَن سَيَكُونُ مِنكُم مَّرۡضَىٰ وَءَاخَرُونَ يَضۡرِبُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ يَبۡتَغُونَ مِن فَضۡلِ ٱللَّهِ وَءَاخَرُونَ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۖ فَٱقۡرَءُواْ مَا تَيَسَّرَ مِنۡهُۚ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُواْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَقۡرِضُواْ ٱللَّهَ قَرۡضًا حَسَنٗاۚ وَمَا تُقَدِّمُواْ لِأَنفُسِكُم مِّنۡ خَيۡرٖ تَجِدُوهُ عِندَ ٱللَّهِ هُوَ خَيۡرٗا وَأَعۡظَمَ أَجۡرٗاۚ وَٱسۡتَغۡفِرُواْ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٠

19. Lalle wannan waʾazi ne, saboda haka duk wanda ya ga dama sai ya kama hanya zuwa ga Ubangijinsa.

20. Lalle Ubangijinka Yana sane da cewa kai kana tsayawa ƙasa da kashi biyu cikin uku na dare, da kuma rabinsa, da kuma ɗaya bisa ukunsa, kai da wata jamaʾar da take tare da kai. Allah ne kuma Yake ƙaddara dare da rana. Ya san kuma cewa, ba za ku iya ƙididdige (sa'o'insa) ba, don haka sai Ya yafe muku; to sai ku karanta abin da ya sauƙaƙa daga Alƙurʾani. Ya san cewa daga cikinku akwai waɗanda za su kasance marasa lafiya, waɗansu kuma suna tafiya a bayan ƙasa don fatauci suna neman falala daga Allah, waɗansu kuma suna yin yaƙi saboda Allah; to sai ku karanta abin da ya sauƙaƙa daga gare shi (Alƙurʾani). Ku kuma tsayar da salla, ku kuma ba da zakka, kuma ku bai wa Allah rance kyakkyawa. Kuma abin da kuka gabatar wa kanku na wani alheri, to za ku same shi wurin Allah, shi ya fi alheri ya kuma fi girman lada. Ku kuma nemi gafarar Allah; lalle Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, dukkan bayanan da suka gabata a wannan Sura da abin da ta ƙunsa na ban tsoro da azaba a ranar lahira, waʾazi ne wanda muminai ne kaɗai za su amfana da su. Don haka duk wanda yake son ya riƙi hanyar da za ta sadar da shi da Ubangijinsa, to sai ya riƙi wannan waʾazi da Surar ta zo da shi, ya bi shariʾar Allah sau da ƙafa da koyarwar Manzon Allah (ﷺ).

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani sauƙi da rangwame da ya yi wa Manzonsa (ﷺ) da alʾummarsa masu koyi da shi wajen Ƙiyamul Laili, tare da tabbatar masa cewa, yana sane da yanayin tsayuwarsa wadda ba ta kai biyu bisa uku na dare ba, wani lokaci kuma rabin dare ne, wani lokaci kuma ɗaya bisa ukunsa; wata jamaʾa ta muminai da suke tare da shi su ma suna koyi da shi a irin wannan tsayuwar. To Allah shi ne yake ƙaddara dare da yini, yake kuma ƙididdige saʾoʾinsu, ya kuma san Annabi (ﷺ) da muminai ba za su iya ƙididdige su ba, don haka sai suke shan wahala wajen tsayuwa a mafi yawan dare domin su cim ma abin da suke buƙata na tsawon lokacin tsayuwarsu. To sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da su cewa, ya sassauta musu, ya kuma yafe musu, don haka suna iya sallatar duk abin da ya sauwaƙa cikin dare.

An karɓo daga Saʾad ɗan Hisham ya ce: Na tambayi Aʾisha (Allah ya ƙara mata yarda) cewa, ta ba ni labarin sallar dare ta Manzon Allah (ﷺ). Sai ta ce: "Ba ka karanta *Ya Ayyuhal Muzzammil ne*?" Sai na ce: Ina yi. Sai ta ce: "To Allah mai girma da buwaya ya farlanta tsayuwar dare a farkon wannan Sura, Annabi (ﷺ) da sahabbansa suka shekara suna tsayuwar dare. Allah ya riƙe ƙarshen Surar bai saukar da shi ba har tsawon wata goma sha biyu, sai kuma a ƙarshen Surar Allah ya saukar da rangwame game da haka, sai tsayuwar dare ta koma taɗawwaʾi bayan tana farilla." [Muslim #746].

Sannan kuma sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata hikimar wadda ta sanya ya yi musu sassauci wajen ƙaddara lokacin tsayuwarsu, watau ta yin laʾakari da wasu abubuwa guda uku da rayuwar alʾumma take da buƙata:

Na farko, marasa lafiya waɗanda ba za su iya tsayuwar rabin dare ba ko biyu bisa uku ko ɗaya bisa ukunsa, to waɗannan sai su yi abin da ya sauwaƙa a gare su. Kuma ko sallar farilla idan mutum ba zai iya tsayawa ba sai ya yi ta a zaune, ita ma nafilar yana iya barin ta ɗungurungum idan za ta wahalar da shi, yana kuma da ladan abin da ya saba yi yana da lafiya.

Na biyu, akwai matafiya masu balaguro don fatauci a bayan ƙasa, to su ma an sassauta musu, har a sallolinsu na farilla ma za su yi ƙasaru, watau rakaʾa bibbiyu a salloli masu rakaʾa huɗu.

Na uku, su ne mayaƙa masu fita don yaƙi da kafirai saboda Allah, don ɗaukaka kalmar Allah.

To duk waɗannan, tsayuwar dare kamar yadda suka saba a da za ta yi musu wahala, don haka sai su sallaci abin da ya sauwaƙa na dare ba tare da sun matsa wa kansu ba.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci bayinsa da tsayar da sallolin farilla kamar yadda ya kamata, su kula da lokutansu da rukunansu da wajibansu da sunnoninsu, su kuma bayar da zakkar dukiyoyinsu, sannan su ba wa Allah kyakkyawan rance, watau su ciyar da dukiyoyinsu don Allah a wuraren da suka dace, ya kuma nuna musu cewa, duk wani aikin alheri da za su yi domin amfanin kawunansu za su sami ladansa a wurin Allah fiye da aikin nasu, domin zai ninninka musu shi. Su kuma nemi gafarar Allah, lalle Allah mai gafarta wa wanda ya tuba daga bayinsa ne, mai jin ƙansu ne.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Zaburar da Manzon Allah (ﷺ) da ya miƙe tsaye domin ya yi kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Tabbatar da manzancin Annabi (ﷺ).

3. Farkon abin da ya wajaba a kan kowane manzo da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika shi ga mutanensa shi ne ya tashi ya gargaɗe su game da azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Wajabcin girmama Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta hanyar bauta masa shi kaɗai ba tare da wani abokin tarayya ba.

5. Wajabcin tsarkake zukata da tufafi da jiki daga duk wata najasa ta zahiri da ta baɗini.

6. Hana mutum ya kyautata wa mutane domin ya samu kyautar da ta fi wadda ya bayar.

7. Wajabcin yin haƙuri da juriya game da wahalhalun daʾawa zuwa ga Allah.

8. Tabbatar da busa ƙaho na tashin alƙiyama.

9. Tabbatar da tsananin ranar alƙiyama ga kafirai da sauƙinta ga muminai



74-Suratul Muddassir

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Muddassir'*. Lafazin *Al-Muddassir* yana nufin wanda ya lulluɓa da mayafi, watau Manzon Allah (ﷺ), kamar yadda bayani zai zo nan gaba.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Babu saɓani a tsakanin malamai a kan cewa Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta biyu (2) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, bisa ga magana mafi inganci, ta sauka bayan '*Suratul Alaƙ'* kafin *'Suratul Muzzammil*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta hamsin ne da shida (56) a lissafin mutanen Basra da Kufa da lissafin farko na mutanen Madina. Amma a lissafin mutanen Sham da lissafin ƙarshe na mutanen Madina adadinsu hamsin da biyar ne (55).

5. Sababin Saukarta:
Ibn Shihab Az-Zuhri ya ce: Abu Salama ɗan Abdurrahman ya ba ni labari cewa, yayin da Jabiru ɗan Abdullahil Ansari yake ba da labarin yankewar wahayi ya ce: (Annabi (ﷺ) ya ce:) "Ina cikin tafiya sai na ji wata murya daga sama, sai na ɗaga idona sai ga Mala'ikan nan da ya zo mini a kogon Hira, yana zaune a kan wata kujera a tsakanin sama da ƙasa. Sai tsoro ya kama ni. Sai na koma gida na ce: "Ku lulluɓe ni", sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "Ya kai mai lulluɓa. Tashi ka yi gargaɗi." To daga nan kuma sai wahayi ya ci gaba da sauka a kai a kai." [Bukhari #4 da Muslim #161].

6. Babban Jigonta:
Surar tana zaburar da Manzon Allah (ﷺ) ne a kan tashi tsaye don kira zuwa ga Allah, tana kuma gargaɗin masu ƙaryata gaskiya da tsoratar da su azabar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Umarni ga Manzon Allah (ﷺ) da ya miƙe tsaye ya gargaɗi mutane ya isar musu da saƙon Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Umartar Ma'aiki (ﷺ) da ya tsarkake zuciyarsa da tufafinsa, ya nisanci bautar gumaka.
• Umartar sa da yawaita sadaka da haƙuri a kan duk wata tsangwama da za a nuna masa.
• Gargaɗin mushirikai da tsoratar da su ranar alƙiyama.

• Gargaɗin duk wani mai sukan Alƙur’ani mai butulce wa ni’imomin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Bayanin siffofin wutar Saƙara.
• Mayar da martani ga mushirikai masu izgili da adadin mala’iku masu tsaron wutar Jahannama.
• Kalubalantar ma’abota littafi da cewa, sun jahilci adadin mala’iku masu tsaron wuta, da cire musu ƙaunar samun tsira daga azabar lahira.
• Bayanin halin muminai ma’abota salla da zakka da ba da gaskiya da ranar sakamako.

Suratul Muddassir (1-10

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلْمُدَّثِّرُ ۝١ قُمْ فَأَنذِرْ ۝٢ وَرَبَّكَ فَكَبِّرْ ۝٣ وَثِيَابَكَ فَطَهِّرْ ۝٤ وَٱلرُّجْزَ فَٱهْجُرْ ۝٥ وَلَا تَمْنُن تَسْتَكْثِرُ ۝٦ وَلِرَبِّكَ فَٱصْبِرْ ۝٧ فَإِذَا نُقِرَ فِى ٱلنَّاقُورِ ۝٨ فَذَٰلِكَ يَوْمَئِذٍ يَوْمٌ عَسِيرٌ ۝٩ عَلَى ٱلْكَـٰفِرِينَ غَيْرُ يَسِيرٍ ۝١٠

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya kai mai lulluɓa.

2. Tashi ka yi gargaɗi.

3. Kuma ka girmama Ubangijinka

4. Ka kuma tsarkake tufafinka.

5. Ka kuma ƙaurace wa (bautar) gumaka .

6. Kada kuma ka goranta wa (Ubangijinka) da ganin yawan (ayyukanka na ƙwarai).

7. Ka kuma yi haƙuri game da Ubangijinka.

8. To idan an busa ƙaho.

9. To wannan ranar rana ce mai tsanani.

10. A kan kafirai, ba mai sauƙi ba ce.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da kiran Manzonsa Muhammadu (ﷺ) wanda yake lulluɓe da tufafinsa don tsoron mala’ikan da ya yi ido huɗu da shi a karon farko a kogon Hira, lokacin saukar masa da wahayi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya miƙe tsaye ya yi wa mutanensa gargaɗi game da azabar Allah. Ya kuma umarce shi da ya girmama Ubangijinsa ta hanyar kaɗaita shi da bauta, sannan ya umarce shi da ya tsarkake kansa daga duk wani zunubi da tufafinsa daga duk wata najasa. Sannan ya umarce shi da ya nisanci na'urar gumaka, ya kuma hana shi ya goranta wa Ubangijinsa ta hanyar ya riƙa ganin yawan kyawawan ayyukansa, watau kada yawansu ya ruɗe shi, ya yi rauni wajen tsayuwa a kan ayyukan da’awa, kuma ya sani duk yawan aikinsa da nagartarsu wata baiwa ce daga Allah a gare shi.
A wani tafsirin kuwa, ana yi masa hani ne game da yin kyauta don a saka masa da mafi yawanta, ko ya yi wa mutane alheri daga baya ya goranta musu.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da ya yi haƙuri a kan cutarwar da za a yi masa.

Haka kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan sakamakon kafirai a ranar alƙiyama, yayin da mala’ika zai busa ƙaho busa ta biyu, to wannan rana ce mai tsanani, ba mai sauƙi ce a kan kafirai ba, domin za su fitar da duk wani tsammani game da samun kuɓuta daga azaba ko rabauta da Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tunatar da ɗan’adam halin da ya shigo duniya a cikinsa, ya zo ne shi kaɗai tilo ba tare da dukiya ko ‘ya’ya ko ilimi ba, daga baya ne Allah yakan ba shi waɗannan ni’imomi don ya gode masa, ya kuma bauta masa shi kaɗai ba tare da yi masa tarayya ba.

2. Alwalidu ɗan Mugira ya fi kowa a Makka yawan dukiya da ‘ya’ya.

3. Saboda mummunar ɗabi'ar kafiri da tsananin son duniyarsa, duk yawan dukiya da tarin ni’imomi da aka yi masa ba zai gushe ba yana hanƙoron neman ƙari.

4. Kasancewar ‘ya’ya maza tare da mahaifinsu koyaushe wata babbar ni’ima ce a gare shi, saboda irin taimako da tallafi da zai samu daga gare su.

5. Kafircin Alwalidu ba na rashin sani ba ne, na girman kai ne da ɗagawa.

6. Kafiran Larabawa sun san Alƙur’ani ba maganar wani mutum ko aljan ba ne; maganar Allah ce, to amma tsananin girman kai da ɗagawarsu ne suka hana su yin imani.

7. Tsananin azabar wutar Saƙara, domin babu wanda zai iya jure wa azabarta.

8. Adadin mala’iku masu tsaron wutar Saƙara su goma sha tara ne.

9. Tabbatar da samuwar mala’iku da bayanin aikin wasu daga cikinsu.

Suratul Muddassir (11-30)
ذَرْنِي وَمَنْ خَلَقْتُ وَحِيدًا ﴿١١﴾ وَجَعَلْتُ لَهُۥ مَالًا مَّمْدُودًا ﴿١٢﴾ وَبَنِينَ شُهُودًا ﴿١٣﴾ وَمَهَّدتُّ لَهُۥ تَمْهِيدًا ﴿١٤﴾ ثُمَّ يَطْمَعُ أَنْ أَزِيدَ ﴿١٥﴾ كَلَّآ ۖ إِنَّهُۥ كَانَ لِـَٔايَٰتِنَا عَنِيدًا ﴿١٦﴾ سَأُرْهِقُهُۥ صَعُودًا ﴿١٧﴾ إِنَّهُۥ فَكَّرَ وَقَدَّرَ ﴿١٨﴾ فَقُتِلَ كَيْفَ قَدَّرَ ﴿١٩﴾ ثُمَّ قُتِلَ كَيْفَ قَدَّرَ ﴿٢٠﴾ ثُمَّ نَظَرَ ﴿٢١﴾ ثُمَّ عَبَسَ وَبَسَرَ ﴿٢٢﴾ ثُمَّ أَدْبَرَ وَٱسْتَكْبَرَ ﴿٢٣﴾ فَقَالَ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا سِحْرٌ يُؤْثَرُ ﴿٢٤﴾ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا قَوْلُ ٱلْبَشَرِ ﴿٢٥﴾ سَأُصْلِيهِ سَقَرَ ﴿٢٦﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا سَقَرُ ﴿٢٧﴾ لَا تُبْقِى وَلَا تَذَرُ ﴿٢٨﴾ لَوَّاحَةٌ لِّلْبَشَرِ ﴿٢٩﴾ عَلَيْهَا تِسْعَةَ عَشَرَ ﴿٣٠﴾

11. Ka bar Ni da wanda Na halitta shi kaɗai.

12. Na kuma yi masa baiwa da dukiya maɗuɗuwa.

13. Da kuma ‘ya’ya masu halartar (tarurruka tare da shi).

14. Na kuma shimfiɗa masa (kyakkyawar rayuwa) iyakar shinfiɗawa

15. Sannan yake kwaɗayin in ƙara (masa).

16. Faufau! Lalle shi ya kasance mai tsaurin kai ne ga ayoyinmu.

17. Ba da daɗewa ba zan ɗora masa (azaba) mai matsananciyar wahala.

18. Lalle shi ya yi tunani, ya kuma auna (a ransa).

19. Sai aka la’ane shi, yaya ya yi irin wannan awon?

20. Sannan aka kuma la’antar sa, yaya ya yi wannan awon?

21. Sannan ya yi nazari.

22. Sannan ya ɗaure fuska, ya kuma murtuke.

23. Sannan ya ba da baya (daga imani) ya kuma yi girman kai.

24. Sai ya ce: “Wannan (Alƙur’ani) ba komai ba ne sai sihiri da aka samo (daga wasu).

25. “Wannan ba komai ba ne sai magana irin ta mutane.”

26. (Allah ya ce): Da sannu zan shigar da shi (wutar) Saƙara.

27. Me ya sanar da kai abin da ake ce wa Saƙara?

28. Ba ta ragewa kuma ba ta barin (komai).

29. Mai ɗaɗɗaye fata ce.

30. Akwai (mala'iku) goma sha tara suna tsaron ta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana a kan ƙasurgumin kafirin nan wanda ya yi suna wajen faɗa da gaskiya da addabar Manzon Allah, watau Alwalidu ɗan Mugira. Wata rana ya ji Annabi (ﷺ) yana karanta Alƙur’ani, sai ya ji kamar yana shigar sa. Da labari ya je kunnen Abu Jahl sai ya ce masa: “Ya kai baffana, mutanenka suna son su tara dukiya su ba ka a kan za ka je ka sami Muhammadu, ka fuskanci abin da yake tare da shi (watau Alƙur’ani).” Sai Alwalidu ya ce: “Lalle Kuraishawa sun san cewa na fi su yawan dukiya.” Sai Abu Jahl ya ce: “Ka faɗi wata magana game da Alƙur’ani da za ta je kunnen mutanenka su fahimci cewa kai ma ba ka yarda da shi ba, kuma ba ka son sa.” Sai ya ce: “To me zan faɗa? A cikinku kakaf babu wanda ya fi ni sanin waƙe-waƙe, wallahi abin da yake faɗa bai yi kama da waƙa ba. Wallahi zancen da yake faɗa yana da zaƙi, kuma tabbas yana da danshi, kuma samansa ya yi ‘ya’ya, ƙasansa kuma a jiƙe yake, kuma lalle shi ne a sama babu abin da ya kere shi.” Sai Abu Jahl ya ce: “Wallahi mutanenka ba za su yarda da kai ba har sai ka soke shi.” Sai ya ce: “Kyale ni in yi tunani a kai.” To bayan ya yi tunani sai ya ce: “Wannan (Alƙur’ani) ba komai ba ne face sihiri da aka samo shi daga wasu.” Sai aka saukar da waɗannan ayoyi. [Abdurrazaƙ, *Tafsir*, juzu’i na 2, shafi na 328, da Al-Hakim #3872].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya faɗa wa Manzonsa (ﷺ) cewa ya bar shi da wannan azzalumi wanda shi ya halicce shi a cikin mahaifiyarsa ba tare da wata dukiya ko ‘ya’ya ba, haka ya zo duniya shi ɗaya tilo, amma Allah ya ci gaba da kulawa da shi har ya kai wani munzali, ya ba shi dukiya mai ɗimbin yawa, ya kuma yi masa baiwar ‘ya’ya maza waɗanda suke tare da shi a koyaushe, suna halartar wuraren tarurruka, ba sa fita ko’ina saboda tarin dukiyarsu, ya kuma hore masa kyakkyawar rayuwa. Duk da waɗannan abubuwa da aka ba shi amma fata yake Allah ya ƙara masa, duk kuwa da yawan kafircinsa. Sai kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna masa cewa faufau, abin da yake tsammani ba mai yiwuwa ne ba, domin shi mutum ne mai taurin kai mai ƙaryata ayoyin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Manzonsa (ﷺ). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, ba da jimawa ba zai haɗa shi da azaba mai tsananin gaske da ba zai iya jure mata ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana irin taurin kan Alwalidu ɗan Mugira, watau duk da irin ɗimbin ni’imar da Allah ya yi masa, amma sai da ya shiga tunanin irin sukar da zai yi a kan Alƙur’ani da ƀatanci, don dai ya lalata shi. Sai da ya tsaya ya auna a ransa tare da zuzzurfan tunani wanda har aka la’ance shi game da wannan awon nasa, aka sake la’antar sa amma bai daina wannan awon a ransa ba. Da ya rasa samun abin suka, don tsabar baƙin ciki da damuwa sai ya ɗaure fuska ya murtuke, a ƙarshe dai ya juya baya ya bijire wa yin imani, ya fito ƙarara ya furta cewa, Alƙur’anin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi sam ba maganar Allah ba ce; sihiri ne kawai, kuma maganar mutane ce wadda ya samu a wurin wasu.Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ambaci mummunan sakamakon da yake jiran Alwalidu a ranar alƙiyama, domin zai shigar da shi wutar Saƙara mai tsananin zafi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya kwarzanta wa Manzonsa (ﷺ) wannan wuta ta Saƙara wadda bai taɓa jin labarinta ba, da cewa ita wuta ce da ba ta rage komai daga jikin wanda aka jefa shi cikinta sai ta cinye shi kakaf, ta lashe shi tas, sannan a sake ɗawo da shi kamar yadda yake da farko, sannan ta sake tasar masa ta cinye shi, haka za ta yi ta yi ba ƙaƙƙautawa. Wuta ce mai tsananin ƙuna, mai saɓule fatar jiki, saboda tsananin zafinta, mala’iku har goma sha tara ne masu tsaron ta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Hikimar ambaton adadin mala’iku masu tsaron wuta.

2. Duk ayyukan Allah ɗauke suke da hikima.

3. Abin da Alƙur’ani ya zo da shi idan ya yi daidai da abin da ya
zo a littafan ma’abota littafi, to wannan wata ƙaƙƙarfar hujja ce a kansu game da gaskiyar Alƙur’ani da Manzon Allah (ﷺ).

4. Imani yana ƙaruwa, dukkan labarun Alƙur’ani kuma suna ƙara wa mumini imani.

5. Zuciya takan yi rashin lafiya kamar yadda gangar jiki take yi.

6. An ba da labarin wani hali na munafukai a nan tare da cewa, lokacin saukar Surar babu su. Wannan yana tabbatar da mu'ujizar Alƙur'ani da gaskiyarsa.

7. Babu wanda ya san iyakacin yawan adadin rundunar Allah sai shi kaɗai. Akwai tsoratarwa babba a cikin wannan, domin Allah zai iya kama mai laifi ta inda bai yi tsammani ba.

Suratul Muddassir (31-37)

وَمَا جَعَلۡنَآ أَصۡحَٰبَ ٱلنَّارِ إِلَّا مَلَٰٓئِكَةٗۙ وَمَا جَعَلۡنَا عِدَّتَهُمۡ إِلَّا فِتۡنَةٗ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ لِيَسۡتَيۡقِنَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ وَيَزۡدَادَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِيمَٰنٗا وَلَا يَرۡتَابَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَلِيَقُولَ ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ وَٱلۡكَٰفِرُونَ مَاذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلٗاۚ كَذَٰلِكَ يُضِلُّ ٱللَّهُ مَن يَشَآءُ وَيَهۡدِي مَن يَشَآءُۚ وَمَا يَعۡلَمُ جُنُودَ رَبِّكَ إِلَّا هُوَۚ وَمَا هِيَ إِلَّا ذِكۡرَىٰ لِلۡبَشَرِ ٣١ كَلَّا وَٱلۡقَمَرِ ٣٢ وَٱلَّيۡلِ إِذۡ أَدۡبَرَ ٣٣ وَٱلصُّبۡحِ إِذَآ أَسۡفَرَ ٣٤ إِنَّهَا لَإِحۡدَى ٱلۡكُبَرِ ٣٥ نَذِيرٗا لِّلۡبَشَرِ ٣٦ لِمَن شَآءَ مِنكُمۡ أَن يَتَقَدَّمَ أَوۡ يَتَأَخَّرَ ٣٧

31. Ba Mu kuwa sanya masu tsaron wutar ba sai mala’iku, ba Mu kuma sanya adadinsu ba sai don fitina ga waɗanda suka kafirta, don kuma waɗanda aka bai wa littafi su sami yaƙini, waɗanda kuma suka yi imani su ƙara imani, waɗanda aka bai wa littafi da muminai kuma kada su yi tababa, don kuma waɗanda suke da raunin imani a zukatansu da kuma kafirai su ce: “Me Allah Yake nufi da yin misali da wannan (adadin)?” Kamar haka Allah Yake ɓatar da wanda Ya ga dama, Yake kuma shiryar da wanda Ya ga dama. Ba kuma wanda ya san (yawan) rundunar Ubangijinka sai Shi. Ita (Saƙara) kuma ba wata abu ba ce face wa’azi ga mutane.

32. A’a. Na rantse da wata.

33. Da kuma dare idan ya ba da baya.

34. Da kuma asuba idan ta bayyana (da haskenta).

35. Lalle ita (Saƙara) tana ɗaya daga manya-manyan (bala’o’i).

36. Gargaɗi ce ga mutane.

37. Ga wanda ya ga dama daga cikinku, ya ci gaba ko ya ci baya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba wasu ne ya sanya tsaron wuta ba sai mala’iku, don haka babu yadda mutane za su ci galaba a kansu, kamar yadda Abu Jahl ya riƙa cika baki yana cewa, shi ko an je lahira aka sanya su a wuta, to za su yi amfani da yawansu da ƙarfinsu murƙushe mala’ikun nan goma sha tara masu tsaron wuta, su fita daga cikin wutar su gudu. Yana kuma faɗar wannan ne cikin izgili da ba'a, domin da ma bai yi imani da ranar lahira ba. Sai kuma Allah ya sanar da su hikimar ambaton wannan adadi na mala’iku ga mutane kashi-kashi kamar haka:
Na ɗaya, ga waɗanda suka kafirta, wannan adadin zai zame musu fitina da jarraba da za ta kai su ga wasu miyagun maganganu na izgili da kafirci wanda zai jawo musu a ninninka musu azaba.
Na biyu, ga ma'abota littafi, watau Yahudawa waɗanda aka ba wa Attaura da Nasara da aka ba wa Injila, su kuma za su ƙara tabbatar da gaskiyar Alƙur'ani, domin za su ga lalle abin da ya zo da shi bai saɓa wa abin da yake cikin littattafansu ba, don haka su da sauran muminai ba za su yi wata tababa a game da gaskiyar Alƙur’ani ba.
Na uku, su kuma muminai imaninsu zai ƙara haɓaka, domin sun ga abin da Alƙur’ani yake bayani yana yin daidai da abin da yake wurin ma'abota littafi.
Na huɗu, waɗanda suke da shakka a zukatansu kuwa da kafirai, za su dabirce ne su riƙa tambayar juna cewa, me Allah yake nufi da ambaton wannan adadi goma sha tara?
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, kamar yadda wasu suke ƙaryata wannan adadi suna izgili da shi, to hakanan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake shiryar da wanda ya ga dama, yake kuma ɓatar da wanda ya ga damar ɓatarwa. Idan kafirai ba su san yawan rundunar Allah ba, ai wannan

ba abin mamaki ba ne, domin babu wanda ya san iya adadin rundunarsa sai shi kaɗai, kuma wuta ba wani abu ce ba face wa’azi ga mutane don su gane girman Ubangijinsu.
Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙaryata kafiran Makka game da maganarsu ta cewa, wai za su yi taron dangi su nuna wa mala’iku masu tsaron wuta cewa, sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi. To Allah ya yi musu rantsuwa da wata da kuma dare yayin da ya ba da baya da duhunsa da kuma asuba idan ta bayyana da haskenta, don ya tabbatar musu cewa, lalle wutar Saƙara tana ɗaya daga cikin manya-manyan bala’o’i, domin gargaɗi ce ga mutane.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kowane mutum a ranar lahira shi ne ke da alhakin ayyukansa da ya aikata a duniya ba wani ba.

2. Haɗarin barin salla ko wasa da ita.

3. Kafirai a lahira za a yi musu azaba a kan ayyukan da aka wajabta musu da ba su aikata ba, kamar salla da zakka.
4. Wajabcin ciyar da miskini ta hanyar ba shi rabonsa a cikin dukiyar zakka, ko yayin da yake cikin matsuwa a taimaka masa.

5. Yana daga cikin abubuwa da suke janyo azabar Allah, kutsawa cikin maganganun ƙarya, kamar ƙaryata ayoyin Allah ko yin izgili ko jayayya a kansu da ƙirƙira wa Allah ƙarya.

6. Karyata ranar alƙiyama da kafirai suka yi shi ya sanya musu gafala da rashin tunawa da mutuwa da raja’a a kan harkokin duniya.

7. Yanayin wutar Jahannama da yanayin waɗanda ake yi wa azaba a cikinta ya sha bamban da yanayin wutar duniya, domin ita wutar lahira duk tsananin azabarta da ƙunarta, mutanen cikinta za su riƙa yi wa juna magana ko su yi wa masu tsaron ta magana ko su roƙi Ubangijinsu, ko su amsa wa ‘yan Aljanna tambayoyinsu, su ma su kira su don su yi musu tambaya. Allah mai iko ne a kan komai.

8. Kore ceto ga kafirai saboda kafircinsu da saɓonsu.

9. Tabbatar da ceto ga muminai masu kaɗaita Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

10. Akwai masu ceto a lahira ban da Manzon Allah (ﷺ).

Suratul Muddassir (38-48)
كُلُّ نَفۡسِۭ بِمَا كَسَبَتۡ رَهِينَةٌ ٣٨ إِلَّآ أَصۡحَٰبَ ٱلۡيَمِينِ ٣٩ فِي جَنَّٰتٖ يَتَسَآءَلُونَ ٤٠ عَنِ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٤١ مَا سَلَكَكُمۡ فِي سَقَرَ ٤٢ قَالُواْ لَمۡ نَكُ مِنَ ٱلۡمُصَلِّينَ ٤٣ وَلَمۡ نَكُ نُطۡعِمُ ٱلۡمِسۡكِينَ ٤٤ وَكُنَّا نَخُوضُ مَعَ ٱلۡخَآئِضِينَ ٤٥ وَكُنَّا نُكَذِّبُ بِيَوۡمِ ٱلدِّينِ ٤٦ حَتَّىٰٓ أَتَىٰنَا ٱلۡيَقِينُ ٤٧ فَمَا تَنفَعُهُمۡ شَفَٰعَةُ ٱلشَّٰفِعِينَ ٤٨

38. Kowane rai jingina ne ga abin da ya tsuwurwurta.

39. Sai dai ga ma'abota dama.

40. (Su kam suna) cikin gidajen Aljanna suna tambayar juna.

41. Game da manyan masu laifuka.

42. (Suna cewa): “Me ya shigar da ku cikin Saƙara?”

43. Suka ce: “Ba mu zama daga cikin masallata ba.

44. “Kuma ba mu kasance muna ciyar da miskini ba.

45. “Mun kuma kasance muna kutsawa (cikin ɓarna) tare da masu kutsawa.

46. “Kuma mun kasance muna ƙaryata ranar sakamako.

47. “Har mutuwa ta zo mana.”

48. Saboda haka ceton masu ceto ba zai amfane su ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, kowane rai a ranar alƙiyama za a jinginar da shi ga ayyukansa, ko dai su hallakar da shi ko kuma su kuɓutar da shi, su ‘yanta shi. Sai dai muminai ma’abota dama, watau waɗanda za su karɓi littattafan ayyukansu ta hannayensu na dama, su kam ba za a kama su da zunubansu ba, za a yafe musu laifukansu ne, saboda kyawawan ayyukansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, su waɗannan muminan a ranar suna cikin gidajen Aljanna suna yi wa junansu tambaya game da kafirai waɗanda suka hallakar da kansu da miyagun ayyukansu. Muminai za su riƙa cewa, mene ne ya shigar da waɗannan kafirai cikin wutar Saƙara? Sai kafiran da kansu su amsa musu da cewa, abubuwa huɗu ne suka jawo musu shiga wannan azabar :
Na ɗaya, a duniya ba su zamanto cikin muminai masu tsayar da salloli na farilla ba, domin ba su yi imani da cewa wajibi ne a kansu su yi salla ba.
Na biyu, ba su zamanto suna ciyar da mabuƙata daga dukiyar da Allah ya ba su ba.
Na uku, sun kasance tare da maɓarnata suna to kutsawa cikin ɓarna, suna faɗar ƙarairayi game da Annabi (ﷺ) da Alƙur’ani da Musulunci da Musulmi, don kawai son ransu.
Na huɗu, sun zamanto suna ƙaryata zuwan ranar alƙiyama, ranar sakamako. Suka kuma ci gaba da ɓarna da ƙaryatawa har mutuwa ta zo musu, aka karɓi rayukansu ba tare da sun tuba sun koma ga Allah ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mutane masu irin waɗannan manyan laifuka, ceton masu ceto a ranar alƙiyama, watau mala’iku da annabawa da salihai, ba zai amfane su ba, domin sharaɗin karɓar ceto shi ne a yarda da wanda za a ceta, su kuwa waɗannan ba su zo da aikin da Allah zai yarda da su ba, don haka za su tabbata a cikin wutar Saƙara.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin bijirewar kafirai daga sauraron wa’azin Manzon Allah (ﷺ).
2. Mummunan halin masu guje wa sauraron wa’azi da tunatarwa da kwatanta halinsu da halin jakunan daji waɗanda suke cike da tsoro da fargabar zaki ko wani mafarauci.

3. Ta’annatin kafirai wajen neman hujja duk kuwa da yawan hujjoji da aka zo musu da su.

4. Imani da ranar lahira shi ne yake sanyawa a ji tsoron azabarta.

5. Babbar manufar saukar da Alƙur’ani ita ce wa’azi da tunatarwa.

6. Tabbatar da ‘*mashi’ar* Allah’, watau babu abin da zai yiwu sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ga damar yiwuwarsa.

7. Tabbatar wa ɗan’adam ‘*mashi’a’*, amma a ƙarƙashin ta Allah. Allah ne ya ba shi damar ya zaɓi hanyar da ya ga dama ya bi, mai kyau ko marar kyau, domin ya gamu da sakamakon aikinsa ba tare da an zalunce shi da komai ba.

8. Babu wanda ya cancanta a bi dokokinsa sau-da-kafa sai Allah, domin shi ne mai gafara ga masu laifi idan sun tuba sun koma gare shi.

Suratul Muddassir (49-56)
فَمَا لَهُمْ عَنِ ٱلتَّذْكِرَةِ مُعْرِضِينَ ﴿٤٩﴾ كَأَنَّهُمْ حُمُرٌ مُّسْتَنفِرَةٌ ﴿٥٠﴾ فَرَّتْ مِن قَسْوَرَةٍۭ ﴿٥١﴾ بَلْ يُرِيدُ كُلُّ ٱمْرِئٍ مِّنْهُمْ أَن يُؤْتَىٰ صُحُفًا مُّنَشَّرَةً ﴿٥٢﴾ كَلَّاۖ بَل لَّا يَخَافُونَ ٱلْءَاخِرَةَ ﴿٥٣﴾ كَلَّآ إِنَّهُۥ تَذْكِرَةٌ ﴿٥٤﴾ فَمَن شَآءَ ذَكَرَهُۥ ﴿٥٥﴾ وَمَا يَذْكُرُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ هُوَ أَهْلُ ٱلتَّقْوَىٰ وَأَهْلُ ٱلْمَغْفِرَةِ ﴿٥٦﴾

49. To me ya same su ne suke bijire wa wa’azi?

50. Kai ka ce su jakunan jeji ne da aka firgitar.

51. Da suka guje wa zaki.

52. A’a, kowane mutum daga cikinsu yana so ne a ba shi takardu buɗaɗɗu (kafin su bi Annabi).

53. Faufau! A’a, su dai ba sa tsoron ranar lahira ne.

54. Tabbas, lalle shi (Alƙur’ani) wa’azi ne.

55. To duk wanda ya ga dama sai ya wa’azantu.

56. Ba sa kuma wa’azantuwa sai idan Allah Ya ga dama. Shi ne Ya cancanci taƙawa, kuma Shi ne Ya cancanci yin gafara.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin kafirai da cewa, me ya same su ne suke bijire wa Alƙur’ani suna bazama duk sanda ake karanta musu shi kamar dai yadda jakunan jeji suke bazama su arce idan sun hango zaki tafe ko wani maharbi mai shirin farautar su.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, tare da irin wannan bijirewa ta kafirai amma kuma kowanne ɗaya daga cikinsu yana son ya wayi gari a daidai kansa ya ga wani buɗaɗɗen littafi wanda zai ba shi labarin cewa Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma fa suna neman haka ne ba domin rashin samun gamsasshiyar hujja ba game da gaskiyar Manzon Allah, sai don tsabar taurin kai da kangara.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, al’amarin ba haka yake ba, abin da kawai yake ƙara musu kafewa a kan ɓarnarsu shi ne saboda ba su yi imani da azabar lahira ba, wannan ya sa suka ci gaba da aikata kafircinsu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, Alƙur’ani wa’azi ne da tunatarwa, don haka duk mai son ya karanta Alƙur’ani ya wa’azantu da shi, to sai ya karanta shi zai ga komai a fili dalla-dalla, to amma ba za su wa’azantu ɗin ba sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ga dama su wa’azantu, domin

komai sai da ganin damarsa yake aukuwa, kuma shi ne ya cancanci a kiyaye dokokinsa, a yi aiki da umarninsa, a guji haninsa, kuma shi ne ya cancanci ya gafarta wa bayinsa zunubansu idan sun tuba sun koma gare shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) yana da iko ya yi rantsuwa da duk abin da ya ga dama a cikin halittunsa don janyo hankalin bayinsa. Amma ba ya halatta ga Musulmi ya yi rantsuwa in ba da Allah ba.

2. Tabbacin aukuwar ranar alƙiyama.

3. Duk wani mumini ransa yana yawan zargin sa, idan mai aikata alheri ne yana zargin sa a kan yana taƙaitawa, yana nuna masa ya kamata ya ƙara sa ƙaimi wajen ayyukan alheri; idan mai aikata mummunan aiki ne, ransa yana zargin sa a kan rashin tuba da komawa ga Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**).

4. Cikar Kudurar Allah a kan komai babu abin da yake gagarar sa.

5. Kafirai suna kawar da kai ne daga ƙwararan dalilai game da alƙiyama don su ci gaba da sheƙe-ayarsu yadda suka ga dama babu mai tsawatar musu.

6. Tsananin tsoro da firgici ga kafirai a ranar alƙiyama.
7. Rushewar tsarin tafiyar rana da wata a ranar alƙiyama.

8. Kafiri a ranar alƙiyama zai nemi wurin gudu yayin da ya ga azabar Allah a fili.

9. Cikar adalcin Allah, domin ba zai kama mai laifi da iliminsa ba, har sai ya kafa masa shaidu daga shi kansa ɗan’adam ɗin, don ya tabbatar da cewa, lalle ya aikata laifuka a duniya.

75-Suratul Kiyama

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara ne da *'Suratul Kiyama'* a cikin littattafan tafsiri da na hadisi da na *mas'hafai*. An kuma kira ta ne da wannan suna saboda an buɗe ta da rantsuwa da ranar alƙiyama.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Babu saɓani a tsakanin malamai cewa Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta talatin da ɗaya (31) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta kuma sauka bayan '*Suratul Kari'a'* kafin '*Suratul Humaza'*.

4. Adadin Ayoyinta:
A wurin malaman Kufa adadin ayoyinta arba'in ne (40), amma a wurin mafi yawancin malaman sauran garuruwa adadinsu talatin da tara ne (39).

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin Kudurar Allah ne a kan sake tattara halittar ɗan'adam da tashin sa bayan mutuwa, domin yi masa hisabi ranar alƙiyama.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tabbatar da tashi bayan mutuwa.
• Tunatarwa game da ranar alƙiyama da alamominta.
• Tabbatar da sakamakon ayyukan da mutane suka aikata a duniya.
• Bayanin 'yan Aljanna da 'yan wuta da karrama 'yan Aljanna.
• Tunatarwa game da mutuwa, kuma ita ce farkon matakan lahira.
• Tsawatarwa game da fifita rayuwar duniya mai ƙarewa a kan rayuwar lahira mai dawwama.

Suratul Ƙiyama (1-15)
لَآ أُقۡسِمُ بِيَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ ١ وَلَآ أُقۡسِمُ بِٱلنَّفۡسِ ٱللَّوَّامَةِ ٢ أَيَحۡسَبُ ٱلۡإِنسَٰنُ أَلَّن نَّجۡمَعَ عِظَامَهُۥ ٣ بَلَىٰ قَٰدِرِينَ عَلَىٰٓ أَن نُّسَوِّيَ بَنَانَهُۥ ٤ بَلۡ
يُرِيدُ ٱلۡإِنسَٰنُ لِيَفۡجُرَ أَمَامَهُۥ ٥ يَسۡـَٔلُ أَيَّانَ يَوۡمُ ٱلۡقِيَٰمَةِ ٦ فَإِذَا بَرِقَ ٱلۡبَصَرُ ٧ وَخَسَفَ ٱلۡقَمَرُ ٨ وَجُمِعَ ٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُ ٩ يَقُولُ ٱلۡإِنسَٰنُ

يَوۡمَئِذٍ أَيۡنَ ٱلۡمَفَرُّ ١٠ كَلَّا لَا وَزَرَ ١١ إِلَىٰ رَبِّكَ يَوۡمَئِذٍ ٱلۡمُسۡتَقَرُّ ١٢ يُنَبَّؤُاْ ٱلۡإِنسَٰنُ يَوۡمَئِذِۭ بِمَا قَدَّمَ وَأَخَّرَ ١٣ بَلِ ٱلۡإِنسَٰنُ عَلَىٰ نَفۡسِهِۦ بَصِيرَةٞ ١٤ وَلَوۡ أَلۡقَىٰ مَعَاذِيرَهُۥ ١٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ina rantsuwa da ranar alƙiyama.

2. Ina kuma rantsuwa da rai mai yawan zargin (kansa).

3. Yanzu mutum yana tsammanin ba za Mu tattara ƙasusuwansa ba?

4. E, (Mu) Masu iko ne a kan Mu daidaita gaɓoɓin yatsunsa.

5. Ba haka ba ne, mutum yana nufi ne kawai ya gurɓata gabansa (da saɓon Allah).

6. Yana tambaya yaushe ne ranar alƙiyamar?

7. To lokacin da gani ya ruɗe.

8. Wata kuma ya yi duhu.

9. Aka kuma haɗe rana da wata (a mafitarsu).

10. A wannan rana ne mutum zai ce: "Ina wurin gudu?"

11. Faufau, babu mafaka.

12. Zuwa ga Ubangijinka ne kawai matabbata take a wannan rana.

13. Za a bai wa mutum labari a wannan rana na abin da ya gabatar da kuma (abin da) ya jinkirtar (na ayyukansa).

14. A'a, shi dai mutum mai shaida ne a kan kansa.15. Ko da kuwa ya kawo uzururrukansa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da ranar alƙiyama, ranar da mutane za su tsaya a gaban Ubangijin talikai don sauraron hukuncinsa. Ya kuma yi rantsuwa da rai mai yawan zargin kansa a kan gazawarsa wajen ayyukan alheri, ko a kan aikata laifuka. Ubangiji ya yi waɗannan rantse-rantse ne domin ya tabbatar da cewa, zai tashi dukkan halittunsa bayan mutuwarsu, domin yi musu hisabi da sakamako.
Sannan Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya zargi ɗan'adam kafiri da cewa, yanzu shi yana zaton Allah ba zai iya tattara ƙasusuwansa ba bayan ya mutu, sun rududduge sun zama turɓaya? Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya mayar masa da martani cewa, haka abin yake, shi mai iko ne a kan ya tattara shi har ma ya dawo masa da gaɓoɓin yatsunsa daidai yadda suke da farko ba tare da an sami wani saɓani ba.
Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) kuma ya bayyana cewa, jayayyar da ɗan'adam kafiri yake yi a kan tashi bayan mutum ba yana yin ta ba ne don rashin samun gamsasshen dalili a kan haka, a'a, kawai dai yana so ne ya ci gaba da sheƙe ayarsa da ayyukan fajirci ba tare da ana tsawatar masa ba, har ma yana

tambaya cikin izgili da rashin kunya cewa, yaushe ne ma alƙiyamar za ta auku ? Watau ba gaskiya ba ce, babu ranar zuwanta a ganinsa.
Sai Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana masa alamomi uku na aukuwarta:
Na ɗaya, lokacin da gani ya ruɗe ya ɗaimauce yayin da zai ga abin da yake ƙaryatawa muraran a gabansa.
Na biyu, yayin da shi kuma wata ya yi duhu, haskensa ya gushe, gushewa ta har abada.
Na uku, aka haɗa rana da wata wuri ɗaya, waɗanda tun lokacin da Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya halicce su ba su taɓa haɗuwa wuri guda ba.
Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tabbatar da cewa, a wannan ranar ne kafiri mai ƙaryata alƙiyama zai riƙa sambatu yana cewa, ina wurin gudu? Sai a ba shi amsa da cewa, faufau, yau babu wurin gudu ko mafaka da zai fake a cikinta. Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, zuwa gare shi kawai makoma take a wannan rana domin yi wa kowa hisabi a kan ayyukansa masu kyau da munana, domin a ranar ne za a ba wa mutum labarin duk abin da ya gabatar na ayyukansa da wanda ya jinkirtar, ban da wannan ma ɗan'adam a ranar shi kansa mai ba da shaida ne a kansa game da munanan ayyukansa da ya aikata, lokacin da gaɓoɓinsa da fatarsa za su ba da shaida a kansa, don haka duk wani hanzari nasa da zai kawo ba zai yi masa amfani ba, domin laifukansa sun riga sun tabbata a kansa kuma lokacin bayar da uzuri a karɓa ya riga ya wuce.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin kwaɗayin Annabi (ﷺ) wajen haddace abin da ake yi masa wahayinsa.

2. Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) yana da damar wajabta wa kansa abin da ya ga dama, amma babu mai wajabta masa komai daga cikin bayinsa.

3. Karatu yana tabbata ne da motsa harshe ba saƙawa kaɗai a zuciya ba.

4. Koyar da ladabin neman ilimi, watau idan malami yana bayanin wata mas'ala ta ilimi, to kada ɗalibi ya yi gaggawar jefo tambaya har sai ya bari malaminsa ya kammala bayaninsa, idan ya gama sai ya tambaye shi abin da bai gane ba.

5. Babu wani abu na Alƙur'ani da ya kuɓuce wa Manzon Allah (ﷺ) da bai isar da shi ga al'ummarsa ba. Ya kiyaye duk wahayin da aka yi masa, ya kuma isar da shi ga al'umma.

6. Duk tsawon rayuwar duniya mai saurin ƙarewa ce, lahira ita ce matabbata ta har abada.

7. Muminai za su ga Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) a ranar alƙiyama, kuma wannan ita ce mafi girman ni'imar da za a ba su a lahira.

Suratul Ƙiyama (16-25)
لَا تُحَرِّكۡ بِهِۦ لِسَانَكَ لِتَعۡجَلَ بِهِۦٓ ١٦ إِنَّ عَلَيۡنَا جَمۡعَهُۥ وَقُرۡءَانَهُۥ ١٧ فَإِذَا قَرَأۡنَٰهُ فَٱتَّبِعۡ قُرۡءَانَهُۥ ١٨ ثُمَّ إِنَّ عَلَيۡنَا بَيَانَهُۥ ١٩ كَلَّا بَلۡ تُحِبُّونَ ٱلۡعَاجِلَةَ ٢٠ وَتَذَرُونَ ٱلۡأٓخِرَةَ ٢١ وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٖ نَّاضِرَةٌ ٢٢ إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٞ ٢٣ وَوُجُوهٞ يَوۡمَئِذِۭ بَاسِرَةٞ ٢٤ تَظُنُّ أَن يُفۡعَلَ بِهَا فَاقِرَةٞ ٢٥

16. (Allah ya ce da Annabinsa): Kada ka motsa harshenka da shi (Alƙur'ani) don gaggauta (karanta) shi.

17. Lalle tattara shi (a zuciyarka) da karanta shi yana kanmu.

18. Saboda haka idan Muka karanta (maka) shi sai ka bi karatunsa.

19. Sannan kuma bayaninsa yana kanmu.

20. Haba, ku dai kawai kuna son duniya ne.

21. Kuna kuma barin lahira.

22. Wasu fuskokin a wannan rana a ni'imce suke.

23. Suna masu kallon Ubangijinsu.

24. Wasu fuskokin kuma a wannan rana a ɗaɗɗaure suke.

25. Suna tabbatar da cewa, za a saukar musu da wani bala'i.

A waɗannan ayoyi Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana tsananin kwaɗayin Manzonsa (ﷺ) wajen sauraron ayoyin Allah da ake saukar masa, da ƙoƙarinsa na son ya gaggauta haddace su don isar da su ga mutanensa. Wannan ya sanya shi yana wahala matuƙa, to sai Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya nusar da shi cewa, kada ya riƙa motsa harshensa da karatun Alƙur'ani yayin da ake yi masa wahayinsa, don ya gaggauta haddace shi don kada ya kuɓuce masa. Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tabbatar masa cewa, ya yi masa alƙawarin zai tattara masa shi a zuciyarsa, ya tabbatar masa da karatunsa a kan harshensa, ba zai manta shi ba, don haka idan Mala'ika Jibrilu yana karanta masa, to ya tsaya tsit ya saurare shi, to sannan Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya yi masa alƙawarin fassara masa shi daki-daki.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) yana shan wahala wajen karɓar wahayin Alƙur'ani, sai ya kasance yana motsa harshensa da leɓensa don kada ya kuɓuce masa, yana son ya haddace shi, sai Allah ya saukar da faɗarsa: "Kada ka motsa harshenka da shi (Alƙur'ani) don gaggauta (karanta) shi. Lalle tattara shi (a zuciyarka) da karanta shi yana kanmu." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya zamanto bayan haka idan Jibrilu ya zo masa, sai ya sunkuyar da kansa ya riƙa sauraron sa, idan ya tafi sai ya karanta Alƙur'ani kamar yadda Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya yi masa alƙawari. [Bukhari #4927 da Muslim #5044].

Sai kuma Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya soki mushirikai, ya bayyana dalilin da ya sanya su ba sa son maganar ranar alƙiyama, har kuma suke riya cewa babu tashi bayan mutuwa duk kuwa da sun san cewa, wanda ya ƙagi halittarsu da farko, ai tashin su bayan mutuwa ba abu ne da zai gagare shi ba, to amma suna ƙaryatawa ne saboda yadda suke tsananin son rayuwar duniya mai saurin gushewa, da watsi da suka yi da rayuwar lahira wadda hanyar samun ta shi ne bin umarnin Allah da guje wa haninsa.
Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana musu kasuwar mutane a ranar lahira kashi biyu:
Kashi na farko, su ne muminai 'yan Aljanna waɗanda fuskokinsu za su yi haske da hasken imani, su ne kuma masu ganin Ubangijinsu (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ba tare da wani shamaki ba.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mun ce: "Ya Manzon Allah, shin za mu ga Ubangijinmu a ranar alƙiyama?" Sai ya ce: "Shin za ku sha wahala wajen ganin rana a lokacin azahar sama fayau babu wani girgije?" Sai muka ce: "A'a, ya Manzon Allah." Sai ya ce: "Shin za ku sha wahala wajen ganin wata daren goma sha huɗu sama fayau babu wani girgije?" Sai suka ce: "A'a, ya Manzon Allah." Sai ya ce: "Ba za ku sha wahalar ganin sa ba a ranar alƙiyama, kamar yadda ba kwa shan wahala wajen ganin rana ko wata." [Bukhari #458 da Muslim #182].

Kashi na biyu, su ne kafirai ‘yan wuta waɗanda fuskokinsu za su murtuke cikin ƙasƙanci, za su tabbatar da cewa, za a saukar musu da azaba mai girma mai tsanani.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tunatarwa game da mutuwa.

2. Wahalar da ke cikin fitar rai yayin mutuwa.

3. Kafiri yayin da ya zo mutuwa zai shiga cikin wahala ne don tsallakawa zuwa tsananin wahalar lahira, don haka a nan ne wahalhalun duniya da na lahira za su haɗe masa wuri guda.

4. Idan ajali ya zo babu wani magani ko addu’a da za ta amfani bawa ta hana shi mutuwa.

5. Za a kama kafirai da rashin bautar Allah da ba su yi ba a duniya, kamar rashin salla.

6. Haɗarin girman kai da taƙama musamman idan ya haɗu da bijire wa gaskiya da juya mata baya.

Suratul Ƙiyama (26-35)
كَلَّآ إِذَا بَلَغَتِ ٱلتَّرَاقِيَ ٢٦ وَقِيلَ مَنۡۜ رَاقٖ ٢٧ وَظَنَّ أَنَّهُ ٱلۡفِرَاقُ ٢٨ وَٱلۡتَفَّتِ ٱلسَّاقُ بِٱلسَّاقِ ٢٩ إِلَىٰ رَبِّكَ يَوۡمَئِذٍ ٱلۡمَسَاقُ ٣٠ فَلَا صَدَّقَ وَلَا صَلَّىٰ ٣١
وَلَٰكِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ٣٢ ثُمَّ ذَهَبَ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِۦ يَتَمَطَّىٰٓ ٣٣ أَوۡلَىٰ لَكَ فَأَوۡلَىٰ ٣٤ ثُمَّ أَوۡلَىٰ لَكَ فَأَوۡلَىٰٓ ٣٥

26. Ku saurara, yayin da rai ya iso a karankarama.

27. Aka kuma ce: “Wane ne mai tawaida?”

28. Ya kuma tabbata cewar (wannan) shi ne rabuwarsa (da duniya).

29. Kuma tsananin bala'i ya haɗu.

30. To zuwa Ubangijinka ne (za a) kora ka a wannan ranar.

31. To bai ba da gaskiya ba bai kuma yi salla ba.

32. Sai dai ya ƙaryata ya kuma ba da baya.

33. Sannan ya tafi zuwa ga iyalinsa yana taƙama.

34. (Azaba) ta doso ka, ta fa doso ka!

35. Sannan ta doso ka, ta fa doso ka!

A waɗannan ayoyi Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana ƙarshen rayuwar kowane ɗan’adam a duniya, don ya tabbatar wa mushirikai cewa, abin ba kamar yadda suke tsammani ba ne cewa, idan sun mutu ba za a yi musu wata azaba ba. Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana cewa, lokacin da rai zai zo

ga karankarama, watau ƙasusuwan ƙirji a lokacin gargarar mutuwa, masu jinya su riƙa tambayar junansu cewa, wane ne zai yi masa ruƙuya ko ya sami sauƙi? A lokacin shi kuma ya tabbatar cewa, lokacin rabuwa da duniya ta zo, watau mutuwa, ga shi kuma tsananin balaʾi ya haɗu, rai ya zo fita daga gangar jiki, to yayin da haka ta faru ne za a kora mamaci zuwa ga Ubangijinsa, to a nan komai zai bayyana ƙarara ga mutum.
Sai Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana mawuyacin halin da kafiri zai samu kansa ciki a ranar domin ya je wa Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) da kafircinsa da taurin kansa, bai gaskata Allah da Manzonsa ba, bai yi salla domin Allah ba, duniya kawai ta ruɗe shi ya ƙaryata abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo masa da shi, ya bijire wa ɗaʾa ga Allah da Manzonsa hankalinsa a kwance babu tsoron Allah ko kaɗan a zuciyarsa, bugu da ƙari kuma yayin da yake juya baya cikin iyalinsa yana taƙama, wannan ya nuna babu abin da yake damun sa.
Sai Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya yi masa alƙawarin narkon azaba cewa, yana nan ya doso shi yana dab da ya auka masa. Allah ya nanata masa wannan narkon don ya tabbatar da cewa, babu makawa sai ya same shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda ya yi imani da cewa, Allah ba ya yin wani abu sai da hikima, to dole ne ya yarda da cewa akwai ranar tashin alƙiyama don yi wa mutane hisabi a kan ayyukansu.

2. Halittar ɗanʾadam a mataki-mataki, tana nuna cikar Ƙudurar Allah a kan aikata duk abin da ya so.

3. Halittar ɗanʾadam ta farko babban dalili ne a kan ikonsa wajen raya matattu.

Suratul Ƙiyama (36-40)
أَيَحْسَبُ ٱلْإِنسَٰنُ أَن يُتْرَكَ سُدًى ﴿٣٦﴾ أَلَمْ يَكُ نُطْفَةً مِّن مَّنِىٍّ يُمْنَىٰ ﴿٣٧﴾ ثُمَّ كَانَ عَلَقَةً فَخَلَقَ فَسَوَّىٰ ﴿٣٨﴾ فَجَعَلَ مِنْهُ ٱلزَّوْجَيْنِ ٱلذَّكَرَ وَٱلْأُنثَىٰٓ ﴿٣٩﴾
أَلَيْسَ ذَٰلِكَ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يُحْۦِىَ ٱلْمَوْتَىٰ ﴿٤٠﴾

36. Yanzu mutum yana tsammanin za a bar shi haka sasakai?

37. Shin bai kasance wani ɗigo na maniyyi da ake zuba shi (a mahaifa) ba?

38. Sannan ya zama gudan jini sannan (Allah) Ya halicce (shi) sai Ya daidaita (shi)?

39. Sannan Ya halicci dangi biyu daga gare shi, namiji da mace?

40. Yanzu wannan bai zama Mai iko a kan ya raya matattu ba?

A waɗannan ayoyi Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) yana tunatar da kafiri mai ƙaryata tashi bayan mutuwa wasu dalilai biyu masu tabbatar da tashin alƙiyama da yi wa mutane hisabi.
Na farko, shin kafiri yana zaton cewa, Allah da ya halicce shi zai bar shi hakanan sakaka babu umarni babu hani, watau ya ƙyale shi ya yi abin da ya ga dama ba tare da zuwan ranar da zai ga sakamakon ayyukansa ba? Lalle wannan zaton banza ne a wurin duk wani mai hankali, domin bai dace da aikin mai hikima ba kamar Allah.
Na biyu, Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tambaye shi cewa, ashe ba shi ne wata rana ya zamanto ɗigon maniyyi wanda ake zuba shi a cikin mahaifa ba? Bayan haka kuma ya zama gudan jini daskararre, sannan

Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya halicce shi ya kuma daidaita halittarsa, ya sanya shi jinsi biyu, namiji da mace? To yanzu a tunaninsa, Allah wanda ya halicce shi daga wannan ƙasƙantaccen ruwa ba zai iya sake raya matattu ba don yi musu hisabi? Tabbas Allah mai iko ne a kan komai.

An karɓo daga Musa ɗan Abu A'isha ya ce: Wani mutum ya kasance yana salla a saman gidansa, sai ya zamanto idan ya karanta faɗar Allah: "Yanzu wannan bai zama mai iko a kan ya raya matattu ba?" Sai ya ce: '*Subhanaka Fa Bala'*, (watau tsarki ya tabbata gare ka, haka ne za ka iya). Sai suka tambaye shi game da wannan abu da yake faɗa, sai ya ce: Na ji shi ne daga Manzon Allah (ﷺ). [Abu Dawud #884].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tunatar wa da ɗan'adam asalinsa lokacin da babu wani ɗan'adam samamme. Sannan sai Allah ya samar da Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) daga nan kuma ya samar da zurriyyarsa ta hanyar saduwar namiji da mace.

2. Yana daga cikin hikimar halittar ɗan'adam don a jarraba shi ta hanyar ɗora masa dokokin shari'a don tantance mai biyayya da mai bijirewa.

3. Baiwar da Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya yi wa ɗan'adam ta hore masa ji da gani waɗanda su ne hanyoyin samun duk wani ilimi.

4. Cikar adalcin Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) da falalarsa yayin da ya nuna wa ɗan'adam duk wata hanya ta alheri da duk wata hanya ta sharri domin ya ba shi damar zaɓa wa kansa hanyar da zai bi, ko ya yi imani ko kuma ya kafirce.

5. Bayan isowar kiran manzannin Allah mutane sun kasu ne gida biyu, ko dai muminai ko kuma kafirai.

76-Suratul Insan

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Surar ta shahara da sunan '*Suratul Insan'*. Ana kuma kiran ta '*Suratu Hal Ata Alal Insan'*, kamar yadda ya zo a cikin [Bukhari #891 da Muslim #880].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
An yi saɓani game da inda aka saukar da ita, wasu malamai sun ce *Makkiyya* ce. Wasu kuma sun ce *Madaniyya* ce. Wasu kuma suka ce *Madaniyya* ce sai 'yan wasu ayoyi kaɗan su ne *Makkiyya*. Amma mafi ingancin magana Sura ce *Makkiyya*, domin salonta da ma'anonin da ta ƙunsa suna tabbatar da haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta talatin (30) ko ta talatin da ɗaya (31) a wurin masu cewa *Makkiyya* ce, ta sauka kafin '*Suratul Kiyama*'. Amma a wurin masu ganin *Madaniyya* ce. Ita ce Sura ta tis'in da takwas (98) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratur Rahman*' kafin '*Suratuɗ Ɗalaƙ*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin yayoyinta talatin da ɗaya ne (31).
5. Babban Jigonta:
Surar tana tunatar da ɗan'adam asalinsa da hikimar halittarsa da makomarsa a duniya da lahira. Tana kuma bayyana ni'imomin Aljanna don ƙarfafa wa muminai gwiwa da jan hankalin kafirai zuwa ga Musulunci.

rn6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tunatar wa ɗan'adam cewa, an halicce shi a halin da babu shi, to me ya sa yake musunta sake raya shi bayan mutuwa?
• Tabbatar wa da ɗan'adam cewa, ya wajaba a kansa ya tsantsanta bautarsa ga Allah ya kuma guji bautar wanin Allah.
• Tabbatar da sakamakon 'yan Aljanna da 'yan wuta.
• Bayanin wasu ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa mutane, kamar ni'imar samar da su da ni'imar ba su fahimta da bambance tsakanin alheri da sharri da nuna musu alheri ta hanyar manzannin da ya aiko musu. Daga cikin mutane akwai wanda ya gode wa ni'imar Allah ya kaɗaita shi da bauta, daga cikinsu kuma akwai wanda ya butulce masa, ya bauta wa waninsa.

• Karfafa wa Manzon Allah (ﷺ) gwiwa game da tashi tsaye ya yi kira zuwa ga Allah ya yi haƙuri da abin da zai same shi na muzgunawa da tsangwama. Kada kuma ya yi sako-sako ga kafirai, ya sani cewa manzanci babbar ni'ima ce da Allah ya yi masa, dole ne ya gode masa a kanta, ta hanyar tsayuwa tsayin daka wajen isar da saƙon Allah da mayar da al'amarinsa zuwa gare shi.
• Umarni da ambaton Allah da tsayar da salloli a lokutansu.

Suratul Insan (1-3)

هَلۡ أَتَىٰ عَلَى ٱلۡإِنسَٰنِ حِينٞ مِّنَ ٱلدَّهۡرِ لَمۡ يَكُن شَيۡـٔٗا مَّذۡكُورًا ١ إِنَّا خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ مِن نُّطۡفَةٍ أَمۡشَاجٖ نَّبۡتَلِيهِ فَجَعَلۡنَٰهُ سَمِيعَۢا بَصِيرًا ٢ إِنَّا هَدَيۡنَٰهُ ٱلسَّبِيلَ إِمَّا شَاكِرًا وَإِمَّا كَفُورًا ٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Haƙiƙa wani yanki na zamani ya zo wa mutum yayin da bai zama wani abin ambato ba.

2. Lalle Mun halicci mutum daga maniyyi gamin-gambiza don Mu jarrabe shi, sai Muka sanya shi mai ji mai gani.

3. Lalle Mun bayyana masa hanya, ko dai (ya zama) mai godewa ko kuma mai butulcewa.

Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya buɗe Surar da tabbatar wa ɗan'adam cewa, wani yankin lokaci mai tsawo ya shuɗe masa yayin da babu shi gaba ɗaya, babu kuma wanda ya san shi. Sannan lokacin da Allah ya tashi halittar sa sai ya halicci asalinsa daga yumɓu, watau halittar Annabi Adamu, sannan ya halicci sauran zuriyyarsa da maniyyi gamin-gambiza tsakanin na namiji da na mace, ya bayyana cewa, ya samar da shi ne don ya jarraba shi ya ga ko zai tuna yanayinsa na farko ko kuma zai manta shi ya ruɗu da kansa. Sai ya sanya shi mai ji ne mai ganin abin da aka ɗora masa yin aiki da shi a shari'a.
Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tabbatar da cewa, ya yi wa ɗan'adam cikakken bayanin hanyar shiriya da hanyar ɓata ta hanyar manzanninsa. Saboda haka ko dai ya bi tafarki madaidaici ya zama bawa mai godiya ga Allah ko kuma ya butulce ya bi hanyar ɓata, sai ya zama bawa kafiri mai musunta ayoyin Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da samuwar wutar Jahannama a yanzu da tanadar abin da za a azabatar da kafirai da shi a cikinta.

2. Daga cikin hanyoyin azabtar da kafirai a wutar Jahannama sun haɗa da sarƙoƙi domin ɗaure ƙafafuwansu da kuma ƙuƙumai domin ɗaure hannayensu a wuyayensu.

3. Mutane nagari waɗanda su ne ma'abota dama za su sha giyar Aljanna bayan an gauraya ta da kafur.

4. Abin shan 'yan Aljanna mai yawan gaske ne ba kuma ya yankewa, domin yana ɓuɓɓugowa ne daga wani marmaro mai kwarara wanda su 'yan Aljanna ne da kansu suke gudanar da shi a duk nahiyar da suka ga dama.

5. Zamantowar mutum bawan Allah, wanda ya sadaukar da kansa ga bautar Allah, wani babban matsayi ne a wurin Allah.

6. Wajabcin cika alƙawarin bakance idan ya zamanto na alheri ne. Amma idan na saɓon Allah ne, to ba ya halatta ga mutum ya cika shi.

7. Tsoron ranar alƙiyama da firgicin da yake cikinta yana daga cikin kyawawan ayyukan mutane nagari.

8. Falalar ciyar da mabuƙata da marayu da fursunonin yaƙi, wannan aiki yana daga cikin hanyoyin samun kyakkyawan sakamako da kuɓuta daga azabar wuta a ranar alƙiyama.

9. Muhimmancin ikhlasi, watau yi don Allah da neman yardarsa.

10. Yana daga cikin cikar sadaka mutum ya guji wani tukuici a kanta na godiya ko na yabo. Sai dai ana so ga wanda aka yi masa ihisani ya yi wa wanda ya yi masa shi godiya da kyakkyawar addu'a.

11. Aljanna da abin da yake cikinta sakamako ne na haƙuri a kan ayyukan alheri da guje wa saɓon Allah da juriya game da ƙaddara marar daɗi.

Suratul Insan (4-12)

إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا لِلۡكَٰفِرِينَ سَلَٰسِلَا۠ وَأَغۡلَٰلَا وَسَعِيرًا ۝٤ إِنَّ ٱلۡأَبۡرَارَ يَشۡرَبُونَ مِن كَأۡسٖ كَانَ مِزَاجُهَا كَافُورًا ۝٥ عَيۡنٗا يَشۡرَبُ بِهَا عِبَادُ ٱللَّهِ يُفَجِّرُونَهَا تَفۡجِيرٗا ۝٦ يُوفُونَ بِٱلنَّذۡرِ وَيَخَافُونَ يَوۡمٗا كَانَ شَرُّهُۥ مُسۡتَطِيرٗا ۝٧ وَيُطۡعِمُونَ ٱلطَّعَامَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ مِسۡكِينٗا وَيَتِيمٗا وَأَسِيرًا ۝٨ إِنَّمَا نُطۡعِمُكُمۡ لِوَجۡهِ ٱللَّهِ لَا نُرِيدُ مِنكُمۡ جَزَآءٗ وَلَا شُكُورًا ۝٩ إِنَّا نَخَافُ مِن رَّبِّنَا يَوۡمًا عَبُوسٗا قَمۡطَرِيرٗا ۝١٠ فَوَقَىٰهُمُ ٱللَّهُ شَرَّ ذَٰلِكَ ٱلۡيَوۡمِ وَلَقَّىٰهُمۡ نَضۡرَةٗ وَسُرُورٗا ۝١١ وَجَزَىٰهُم بِمَا صَبَرُواْ جَنَّةٗ وَحَرِيرٗا ۝١٢

4. Lalle Mun tanadar wa kafirai sarƙoƙi da ƙuƙumai da wutar Sa'ira.

5. Lalle mutane nagari suna sha daga wani kofin (giya) da mahaɗinta ya kasance kafur ne.

6. Wani marmaro ne da bayin Allah suke sha daga gare shi suna ɓuɓɓugo shi ɓuɓɓugowa ta haƙiƙa.

7. Suna cika alƙawari na bakance suna kuma tsoron ranar da sharrinta ya kasance mai bazuwa ne.

8. Suna kuma ciyar da abinci tare da suna son sa ga miskini da maraya da kuma ribataccen yaƙi.

9. (Suna cewa): ‘‘Mu kawai muna ciyar da ku ne saboda Allah, ba ma nufin sakamako ko godiya daga wurinka.

10. ‘‘Lalle mu muna jin tsoron rana mai sa ɗaure fuska, matsananciya daga Ubangijinmu.

11. Sai Allah Ya kare su (daga) sharrin wannan ranar Ya kuma ba su haske (a fuskokinsu) da kuma farin ciki.

12. Ya kuma saka musu da Aljanna da alharini saboda haƙurin da suka yi.

A waɗannan ayoyi Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana sakamakon bayinsa bijirarru da waɗanda suka yi masa biyayya a lahira, da cewa ya yi wa waɗanda suka kafirce masa suka bijire wa manzanninsa

tanadin sarƙoƙin da za a ja su da su a cikin wutar Jahannama da ƙuƙumai waɗanda za a haɗa hannayensu da wuyoyinsu a ɗaure su tamau da su. Ya kuma yi musu tanadin wata wuta mai ruruwa. Su kuma mutane nagari waɗanda suka yi wa Allah biyayya a ranar alƙiyama, ya tabbatar musu cewa, a gidajensu na Aljanna za su sha wani cikakken kofi na giya wadda aka gauraya ta da kafur mai daɗin ƙamshi. Wannan abin sha kuma daga wani marmaro ne marar ƙafewa wanda daga gare shi ne bayin Allah suke sha har su ƙoshi; suna ɓuɓɓugo da shi su kwararar da shi zuwa inda suka ga dama.
Sannan Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana kyawawan siffofin waɗannan bayi nasa nagari waɗanda da su ne suka cancanci wancan sakamako:
Na farko, suna cika alƙawari na bakance, watau alƙawarin da suka yi na ɗora wa kawunansu wasu ayyuka na ɗa'a, kamar salloli ko azumi ko sadaka.

An karɓo daga A'isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: Manzon Allah ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya yi bakancen zai yi wa Allah ɗa'a, to ya yi masa, wanda kuma ya yi bakancen zai saɓa wa Allah, to kada ya saɓa masa." [Bukhari #6696].

Na biyu, suna ciyar da abinci tare da cewa suna son sa suna kuma buƙatar sa, amma sai su ba da shi ga mabuƙata da marayu da ribatattun yaƙi.
Na uku, suna yin haka ne kuma da manufarsu ta neman yardar Allah, suna faɗa a ransu cewa, suna ciyar da waɗannan mabuƙata ne kawai don neman yardar Allah, don haka ba sa buƙatar wani sakamako ko godiya daga gare su.
Na huɗu, suna tsoron wata rana da fuskokin 'yan wuta za su murtuke su ɗaure saboda tsananin wannan ranar a gare su.
Sai Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana cewa, ya biya musu dukkan buƙatunsu, ya kuma tsare su da falalarsa daga sharrin wannan ranar, ya kuma haɗa fuskokinsu da haske da annuri don girmama su da shigar musu da farin ciki a zukatansu. Kuma saboda haƙurinsu wajen bin Allah da abin da ya same su na ƙaddararsa sai ya saka musu da gidan Aljanna da za su shiga su more ni'imomin da ke cikinta, ya kuma ba su tufafin alharini wanda za su riƙa sakawa a jikinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. A cikin Aljanna babu rana babu dare, koyaushe haske ne marar gushewa.

2. Duk da cewa babu rana a cikin Aljanna sai haske, to amma akwai inuwoyin bishiyoyin cikinta masu ɗauke da kayan marmari dab-da-dab, ga na kishingiɗe a ƙarƙashinsu.

3. 'Yan Aljanna suna da hadimai matasa waɗanda suke kai-kawo suna yi musu hidima babu gajiyawa a tare da su.

4. Babban abin mamaki a gidajen Aljanna shi ne, ƙoransu da kofunansu na azurfa ne, amma garai-garai suke kamar kwalabe, ana ganin duk abin da yake cikinsu na ci ko na sha.

5. Giyar Aljanna iri-iri ce, daga ciki akwai wadda ake gauraya ta da kafur; akwai kuma wadda ake haɗa ta da citta mai yatsu.

6. Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya siffanta hadiman 'yan Aljanna da matuƙar kyau da annuri, to ina kuma ga su 'yan Aljannar? Babu shakka kyansu ya wuce a misalta.

7. Hadiman 'yan Aljanna masu yawa ne sosai.

8. Mulkin da Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) zai bai wa ‘yan Aljanna mulki ne ƙasaitacce mai girman gaske, domin mutum ɗaya daga cikinsu zai zamanto yana da manya-manyan gine-gine na alfahari da gidaje masu cike da ɗakuna sama da ƙasa na gani na faɗa, sannan ga gonaki masu cike da ‘ya’yan itatuwa iri-iri masu matuƙar dadi, ko’ina kuma ga inuwoyi waɗanda ba sa gushewa, ga kuma tsuntsaye kyawawa masu daɗin murya, bugu da ƙari kuma, ga mata da Allah zai ba shi masu tsalelen kyau da kyawawan halaye da biyayya ga mazajensu, ta ɓangare guda kuma ga yara matasa hadimai kyawawa waɗanda ba sa tsufa, suna ta yi masa hidima ba dare ba rana. Abin da ya fi duk waɗannan ni’imomi dadi kuwa shi ne dace da samun yardar Allah ta har abada da ganin fuskarsa mai girma. Tsarki ya tabbata ga Allah mamallakin mulki wanda yake ba da mulkinsa ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, taskokinsa na alheri kuma cike suke koyaushe ba sa raguwa, alheransa ga masoyansa sun fi ƙarfin a sifanta su.

Suratul Insan (13-22)

مُّتَّكِـِٔينَ فِيهَا عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِۖ لَا يَرَوۡنَ فِيهَا شَمۡسٗا وَلَا زَمۡهَرِيرٗا ١٣ وَدَانِيَةً عَلَيۡهِمۡ ظِلَٰلُهَا وَذُلِّلَتۡ قُطُوفُهَا تَذۡلِيلٗا ١٤ وَيُطَافُ عَلَيۡهِم بِـَٔانِيَةٖ مِّن فِضَّةٖ وَأَكۡوَابٖ كَانَتۡ قَوَارِيرَاْ ١٥ قَوَارِيرَاْ مِن فِضَّةٖ قَدَّرُوهَا تَقۡدِيرٗا ١٦ وَيُسۡقَوۡنَ فِيهَا كَأۡسٗا كَانَ مِزَاجُهَا زَنجَبِيلًا ١٧ عَيۡنٗا فِيهَا تُسَمَّىٰ سَلۡسَبِيلٗا ١٨ ۞وَيَطُوفُ عَلَيۡهِمۡ وِلۡدَٰنٞ مُّخَلَّدُونَ إِذَا رَأَيۡتَهُمۡ حَسِبۡتَهُمۡ لُؤۡلُؤٗا مَّنثُورٗا ١٩ وَإِذَا رَأَيۡتَ ثَمَّ رَأَيۡتَ نَعِيمٗا وَمُلۡكٗا كَبِيرًا ٢٠ عَٰلِيَهُمۡ ثِيَابُ سُندُسٍ خُضۡرٞ وَإِسۡتَبۡرَقٞۖ وَحُلُّوٓاْ أَسَاوِرَ مِن فِضَّةٖ وَسَقَىٰهُمۡ رَبُّهُمۡ شَرَابٗا طَهُورًا ٢١ إِنَّ هَٰذَا كَانَ لَكُمۡ جَزَآءٗ وَكَانَ سَعۡيُكُم مَّشۡكُورًا ٢٢

13. Suna masu kishingiɗa a cikinta a kan gadaje; ba sa ganin rana ko jin tsananin sanyi a cikinta.

14. Inuwoyinta kuma suna kusa da su, an kuma hore musu 'ya'yan itatuwanta matuƙar horewa.

15. Ana kuma kai-kawo a tsakaninsu da ƙorai na azurfa da kofuna waɗanda suka kasance na ƙarau.

16. Ƙarau dîn na azurfa ne, sun auna su, aunawa daidai da buƙata.

17. Ana kuma shayar da su wata giya a cikinta, wadda mahadînta ya kasance citta mai yatsu ce.

18. Wani marmaro ne a cikinta da ake kiran sa *Salsabilu*.

19. Samari hadimai dawwamammu (da ba sa tsufa) kuma suna kai-kawo tsakaninsu, idan ka gan su sai ka yi tsammanin su wani lu’ulu’u ne da aka baza.

20. Idan kuma ka yi kallo a can, za ka ga ni’ima da kuma mulki ƙasaitacce.

21. Suna sanye da korayen tufafin alharini marar kauri da na alharini mai kauri; aka kuma yi musu ado da warawarai na azurfa, Ubangijinsu kuma Ya shayar da su abin sha mai tsarki.

22. Lalle wannan ya kasance sakamako ne a gare ku, kuma aikinku ya kasance abin godewa.

A waɗannan ayoyi Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya ci gaba da bayyana ni’imomin da ya tanadar wa bayinsa nagari a Aljanna, inda ya ambaci cewa a cikin gidajensu na Aljanna ya tanadar musu da gadaje na alfarma waɗanda za su riƙa kishingiɗa a kansu, kuma ba za su ga wata rana a cikin Aljanna ba wadda zafinta zai cutar da su, ba kuma za su ji matsanancin sanyi ba, don haka koyaushe suna cikin inuwa wadda babu zafi a cikinta babu kuma matsanancin sanyi.

Wata ƙarin ni'imar kuma a gare su, ita ce inuwoyin bishiyoyin gidan Aljanna waɗanda suke kusa da su, ba sa janyewa har abada, sannan an hore musu 'ya'yan itatuwanta ga duk mai son ya tsinka zai tsinke su cikin sauƙi ba tare da ya sha wata wahala ba a kowane yanayi kuma yake ciki; a kwance yake ko a zaune ko a tsaye. Kuma hadimai suna kai-kawo a tsakaninsu da ƙorai na azurfa da kuma kofuna na ƙarau garai-garai cike da abin sha. Su waɗannan kofuna na azurfa garai-garai suke kamar ƙarau har ana ganin abin shan da yake cikinsu, hadiman da suke kai-kawo a tsakaninsu kuma suna auna musu abin shan su daidai buƙatarsu, ba sa cika musu kofunan fal har suna zuba, ba kuma sa yi musu ƙwauro ya kasa isar su.
Ana kuma shayar da su wata giya cike da kofi wadda aka gauraya ta da citta mai yatsu, mai daɗin ɗanɗano da ƙamshi. Suna kuma sha daga wani marmaro na Aljanna wanda ake kira **'salsabilu'**.
Sannan Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana siffofin masu kai-kawo suna yi musu hidima a Aljanna da cewa, wasu samari ne waɗanda koyaushe suna cikin ƙuruciyarsu ba sa tsufa; idan mutum ya gan su saboda hasken fuskokinsu da kyan fatar jikinsu da yawansu sai ya yi tsammanin wani lu'ulu'u ne wanda aka baza a ko'ina.
Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya kwarzanta wa Manzonsa ﷺ) bayanin ni'imomin Aljanna da cewa, idan ya ga ni'imomin gidan Aljanna abin ya fi ƙarfin a siffanta shi, domin zai ga ƙasaitaccen mulki yana gudana, zai ga abin da bai taɓa gani ko jin irinsa ba. Kuma ga 'yan Aljanna sanye da tufafi koraye na alfahari waɗanda aka ɗinka su da alharini marar kauri, ga wasu kuma masu kauri, an kuma yi musu ado da warawarai na azurfa, sannan Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya shayar da su wani tataccen abin sha da zai tsaftace musu dukkan jikinsu ciki da waje.
Sai kuma Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana wa muminai cewa, duk waɗannan ni'imomi da aka yi musu bayaninsu an tanade su ne domin su kasance sakamako a gare su a kan kyawawan ayyukansu a duniya, kuma ana yi musu godiya a kan ayyukansu karɓaɓɓu a wajen Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Saukar da Alƙur'ani ga Manzon Allah ﷺ) guntu-guntu wata babbar ni'ima ce a gare shi da kuma al'ummarsa.

2. Wajabcin yin haƙuri a kan bin Allah da guje wa haninsa da haƙuri a kan ƙaddararsa marar daɗi.

3. Da'awa zuwa ga Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) tana buƙatar haƙuri da kau da kai daga duk wani mai saɓon Allah ko kafirai masu ƙoƙarin hana gaskiya yaɗuwa.

4. Ambaton Allah da tsayar da sallolin farilla da yawan tsayuwar dare, suna taimaka wa bawa wajen haƙuri da juriya a kan bin Allah da isar da saƙonsa.

5. Falalar tsayuwar dare a cikin sallolin nafiloli.

6. Falalar sujjada a cikin ayyukan salla.

7. Wautar kafirai da suke fifita son duniya mai ƙarewa a kan lahira mai dawwama.

8. Tsoratar da kafirai ranar alƙiyama wadda za ta zo musu da wahalhalu da musibu iri-iri.

9. Mayar da martani ga masu ƙaryata tashi bayan mutuwa.

10. Baiwar da Allah ya yi wa ɗan'adam a halittar gaɓoɓinsa yayin da ya ba shi ƙarfi domin ya iya aiwatar da al'amuransa na rayuwa.

11. Tabbatar wa ɗan'adam ganin dama, watau '*mashi'a*', wadda ita ce iko da Allah ya ba shi na ya zaɓi hanyar shiriya ko ya zaɓi hanyar ɓata. Amma *mashi'ar* bawa tana ƙarƙashin *mashi'ar* Allah ne, domin babu abin da bawa zai iya yi ba don Allah ya ga damar ya yi hakan ba.

12. Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya riga ya tanadi wutar Jahannama domin azzalumai, tana nan tana jiran su.

Suratul Insan (23-31)

إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا عَلَيْكَ ٱلْقُرْءَانَ تَنزِيلًا ﴿٢٣﴾ فَٱصْبِرْ لِحُكْمِ رَبِّكَ وَلَا تُطِعْ مِنْهُمْ ءَاثِمًا أَوْ كَفُورًا ﴿٢٤﴾ وَٱذْكُرِ ٱسْمَ رَبِّكَ بُكْرَةً وَأَصِيلًا ﴿٢٥﴾ وَمِنَ ٱلَّيْلِ فَٱسْجُدْ لَهُۥ وَسَبِّحْهُ لَيْلًا طَوِيلًا ﴿٢٦﴾ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ يُحِبُّونَ ٱلْعَاجِلَةَ وَيَذَرُونَ وَرَآءَهُمْ يَوْمًا ثَقِيلًا ﴿٢٧﴾ نَّحْنُ خَلَقْنَٰهُمْ وَشَدَدْنَآ أَسْرَهُمْ ۖ وَإِذَا شِئْنَا بَدَّلْنَآ أَمْثَٰلَهُمْ تَبْدِيلًا ﴿٢٨﴾ إِنَّ هَٰذِهِۦ تَذْكِرَةٌ ۖ فَمَن شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلًا ﴿٢٩﴾ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمًا ﴿٣٠﴾ يُدْخِلُ مَن يَشَآءُ فِى رَحْمَتِهِۦ ۚ وَٱلظَّٰلِمِينَ أَعَدَّ لَهُمْ عَذَابًا أَلِيمًا ﴿٣١﴾

23. Lalle Mu Muka saukar maka da Alƙur'ani daki-daki.

24. Saboda haka ka yi haƙuri da hukuncin Ubangijinka kada kuwa ka bi mai yawan saɓo ko mai yawan kafircewa daga cikinsu.

25. Ka kuma ambaci sunan Ubangijinka safe da yamma.

26. Da daddare kuma sai ka yi sujjada a gare Shi, ka kuma yi nafiloli saboda Shi a tsawon dare.

27. Lalle waɗannan suna son mai gaggawar ƙarewa (watau duniya), suna kuma watsi da rana mai nauyi a bayansu.

28. Mu Muka halicce su Muka kuma ƙarfafa gaɓoɓinsu; idan kuwa Muka ga dama sai Mu musanya irinsu (kyakkyawar) musanyawa.

29. Lalle wannan wa'azi ne; saboda haka wanda ya ga dama sai ya riƙi hanya zuwa ga Ubangijinsa.

30. Kuma ba ganin damarku ba ce sai abin da Allah ya ga dama. Lalle Allah Ya kasance Masani, Mai hikima.

31. Yana shigar da wanda Ya ga dama cikin rahamarsa. Azzalumai kuwa Ya tanadar musu azaba mai raɗaɗi.

A waɗannan ayoyi Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) girman matsayin da ya ba shi, domin kuwa shi ne ya saukar masa da Alƙur'ani guntu-guntu, bai saukar masa shi a dunƙule ba lokaci ɗaya, don haka ya ci gaba da riƙo da hukunce-hukuncensa da shari'o'insa, ya isar da su ga al'ummarsa. Ya kuma umarce shi da yin haƙuri da abin da Ubangijinsa zai hukunta masa na shari'a ko na ƙaddara, kada kuma ya biye wa wani mai saɓo a kan abin da yake yi na saɓon Allah, kada kuma ya biye wa wani kafiri a kan kafircinsa, saboda biye musu saɓa wa Allah ne, domin ba za su taɓa kawo wani abu ba sai wanda ya dace da son zuciyarsu.

Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya umarci Manzonsa da ya ambaci Ubangijinsa a sallar asuba da safe da sallar azahar da laʾasar a ƙarshen yini. Ya kuma ambace shi a sallolinsa na dare, watau sallar magariba da sallar isha, sannan ya yi sallolin nafiloli, watau tahajjud a tsawon dare.
Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tabbatar wa Manzonsa ﷺ) cewa, mushirikai ba komai suke so ba in ban da more rayuwar duniya mai saurin ƙarewa, amma suna watsi da rana mai nauyi, watau alƙiyama a bayansu, bayan kuma cike take da wahalhalu da musibu iri-iri, duk da haka sun ƙi yi mata wani kyakkyawan tanadi sai kafirci da saɓon Allah.
Sannan Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya kafa musu ƙwaƙƙwarar hujja ta hankali a kan sake tashin su bayan sun mutu domin yi musu hisabi a ranar alƙiyama da suke ƙaryatawa, Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tabbatar musu cewa, shi ne ya halicce su tun da farko ya kuma ƙarfafa halittarsu ta hanyar ƙarfafa musu gaɓoɓinsu da sauran halittar jikinsu, don haka idan ya ga dama sai ya hallaka su ya kawo wasu irinsu, wannan kuma ba abu ne da zai gagare shi ba. Ko kuma idan ya ga dama sai ya hallaka su ya maye gurbinsu a nan duniya da wasu irinsu waɗanda ba za su saɓa masa ba ko su kafirce masa.
Daga ƙarshen Sura Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana cewa, lalle wannan Sura waʾazi ce da tunatarwa, don haka duk wanda ya ga dama yana iya kama hanya madaidaiciya da za ta sadar da shi da samun yardar Ubangijinsa a ranar alƙiyama. Sannan ya bayyana cewa, mutane ba su ne suke yin abin da suka ga dama ba, sai abin da Allah ya ga damar aukuwarsa, domin komai yana hannunsa, shi ne kuma masanin abin da ya fi dacewa ga bayinsa da wanda bai dace da su ba, mai hikima ne a cikin halittarsa da ƙaddararsa da shariʾarsa. Yana kuma shigar da wanda ya ga dama daga cikin bayinsa a cikin rahamarsa, ya yi musu gamon-katarin imani da ayyuka nagari. Ya kuma tanadar wa azzalumai masu cutar kawunansu da kafirci da laifuka wata azaba mai raɗaɗî a lahira, ita ce azabar wutar Jahannama.
Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:
1. Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) yana iya yin rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittunsa don ya nuna muhimmancinsa ya kuma janyo hankalin bayinsa don ɗaukar izina daga gare shi. Amma ba ya halatta ga wani mutum ya yi rantsuwa ba da Allah ba.

2. Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) ya yi rantsuwa a nan da iska da kuma malaʾiku saboda wata alaƙa da take tsakaninsu, watau iska takan taso ɗauke da rahamar Allah, watau ruwan sama. Su ma malaʾiku sukan sauko da wahayi da ambaton Allah **Mai tsarki da ɗaukaka**) wanda yake raya zukata da shi kamar yadda yake raya ƙasa da ruwan sama.

3. Hikimar saukar wa manzannin Allah wahayi ita ce yanke wa mutane duk wani hanzari a gaban Allah da gargaɗin su da azabarsa **Mai tsarki da ɗaukaka**).
4. Ambaton wasu alamomin tashin alƙiyama waɗanda suka haɗa da tafiyar da hasken taurari da tsattsagewar sama da niƙe duwatsu.

5. Tsoratar da masu ƙaryata ranar alƙiyama da azabar Allah mai tsanani.

77-Suratul Mursalat

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
An fi sanin wannan Sura da '*Suratul Mursalati'*, watau ana mata laƙabi da kalmar farko a cikinta.
A zamanin sahabbai ana kiran ta da sunan '*Suratu Wal Mursalati Urfa'*, kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul Bukhari* #3317 da Sahihu Muslim #2234.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Ummul Fadil (Allah ya kara mata yarda) ta ji shi yana karanta '*Wal Mursalati Urfa'* sai ta ce: "Ya ɗana, wallahi karatun nan naka ya tuna min da karatun Manzon Allah (ﷺ) da na ji shi yana karanta wannan Surar, kuma ita ce ƙarshen abin da na ji Manzon Allah (ﷺ) yana karantawa a sallar magariba." [Bukhari #765 da Muslim #462].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai suna ganin Sura ce *Makkiyya,* tana daga cikin surorin farko da aka saukar wa Manzon Allah (ﷺ) a Makka.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (**Allah ya kara masa yarda**) ya ce: Yayin da muke tare da Manzon Allah (ﷺ) a wani kogo a Mina sai aka saukar masa '*Wal Mursalati'*, yana cikin karanta mini ita, bakinsa yana ɗanye da ita, sai kawai ga wata macijiya ta yiwo kanmu, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku kashe ta." Sai muka yi kanta, sai da sauri ta gudu, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "An tsare ta daga sharrinku, kamar yadda aka tsare ku daga sharrinta." [Bukhari #1830 da Muslim #2234].

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta talatin da uku (33) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Humaza'* kafin '*Suratu Kaf*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta hamsin ne (50) babu wani saɓani.

5. Babban Jigonta:
Tana tabbatar da aukuwar ranar alƙiyama da hujjoji masu ƙarfi, tare da tsoratarwa da gargaɗi ga masu ƙaryatawa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:

• Bayanin dalilin aukuwar tashi bayan mutuwa da wasu daga cikin alamomin alƙiyama.
• Kafa hujja da halittar ƙasa da ta mutum a kan yiwuwar tashi bayan mutuwa da alƙawarin narko ga masu ƙaryatawa.
• Yi wa masu ƙaryata tashin alƙiyama kashedi da aukuwar azaba a kansu tun a nan duniya kamar yadda aka hallakar da al'ummun da suka gabace su.
• Yi wa muminai alƙawarin kyakkyawan sakamako a lahira.
• Yin kira zuwa ga Musulunci da gaskata Alƙur'ani saboda dalilai bayyanannu a kan haka.

Suratul Mursalat (1-15)

وَٱلۡمُرۡسَلَٰتِ عُرۡفٗا ١ فَٱلۡعَٰصِفَٰتِ عَصۡفٗا ٢ وَٱلنَّٰشِرَٰتِ نَشۡرٗا ٣ فَٱلۡفَٰرِقَٰتِ فَرۡقٗا ٤ فَٱلۡمُلۡقِيَٰتِ ذِكۡرًا ٥ عُذۡرًا أَوۡ نُذۡرًا ٦ إِنَّمَا تُوعَدُونَ لَوَٰقِعٞ ٧ فَإِذَا ٱلنُّجُومُ طُمِسَتۡ ٨ وَإِذَا ٱلسَّمَآءُ فُرِجَتۡ ٩ وَإِذَا ٱلۡجِبَالُ نُسِفَتۡ ١٠ وَإِذَا ٱلرُّسُلُ أُقِّتَتۡ ١١ لِأَيِّ يَوۡمٍ أُجِّلَتۡ ١٢ لِيَوۡمِ ٱلۡفَصۡلِ ١٣ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلۡفَصۡلِ ١٤ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ١٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da iska mai bibiyar juna.

2. Da kuma iska mai tasowa da tsanani.

3. Da iska mai watso ruwa watsowa.

4. Da kuma (mala'iku) masu rarrabe ƙarya da gaskiya iya rarrabewa.

5. Sannan masu sauko da wahayi.

6. Don yanke hanzari ko don gargaɗi.

7. Lalle abin da ake yi muku alƙawari tabbas mai afkuwa ne.

8. To idan taurari aka shafe haskensu.

9. Idan kuma sama aka tsattsage ta.

10. Idan kuma duwatsu aka sheƙe su.

11. Idan kuma manzanni aka tattara su.

12. Ga wacce rana ce aka ƙayyaje musu.

13. Ga rana ta yin hukunci.

14. Me kuma ya sanar da kai ranar yin hukunci.

15. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Surar da rantsuwa da wasu muhimman halittunsa masu girma. Ya rantse da iska mai bibiyar juna, da iska mai tasowa da ƙarfi da iska mai watso da ruwa ƙasa. Allah kuma ya yi rantsuwa da mala'iku masu saukowa da abin da yake rarrabe tsakanin gaskiya da ƙarya, watau masu saukowa da wahayi zuwa ga manzannin Allah domin yanke wa bayi hanzari a wurin Allah da wurin mutane ko gargaɗi ga mutane game da azabar Allah.
Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya yi waɗannan rantse-rantse ne don ya tabbatar da cewa, lalle alƙawarin tashi bayan mutuwa da hisabi da sakamako, tabbas mai aukuwa ne babu makawa.
Sai kuma Allah ya ambaci wasu alamomin wannan ranar da cewa, a lokacin da za a ga tsarin gudanar da duniya gaba ɗaya ya rikice, an tafiyar da hasken taurari, sama kuma ta tsattsage, mala'iku suna ta saukowa da umarnin Allah, an tumbuke duwatsu daga wurarensu an dandaƙe su sun zama ƙura an sheƙe su; manzanni kuma an tattara su don wani ƙayyadajjen lokaci na wani yini mai girma, don su ba da shaida game da al'ummunsu cewa, sun isar musu da saƙon Allah, ranar da za a yi hukuncin tsakanin bayi a bayyana mai gaskiya da marar gaskiya da ɗan wuta da ɗan Aljanna.
Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya nuna wa Manzonsa girman wannan rana har ya yi masa tambayar cewa, me ma ya sanar da shi ranar yin hukunci? Sai Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tabbatar da cewa, tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryata manzannin Allah da gaskiyar da suka zo da ita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sunnar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) game da masu ƙaryata manzanninsa ita ce hallakar da su.

2. Kulawar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bai wa ɗan'adam lokacin da yake cikin mahaifar mahaifiyarsa. Wannan wata babbar aya ce mai tabbatar da cikar Kudurar Allah da ikonsa a kan komai.

3. Kasa ta yalwaci dukkan masu rai da waɗanda suka mutu.

4. Nuna wa ɗan'adam baiwar da Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya yi masa ta sanya ƙasa ta zamanto wurin binne shi yayin da ya mutu, tun lokacin da Allah ya kinsa wa ɗaya daga cikin 'ya'yan Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda ya kashe ɗan'uwansa bisa zalunci cewa, ya binne shi a cikin ƙasa kamar yadda ya gabata a **Suratul Ma'aida**, aya ta 31.

5. Wajabcin binne matattu a ƙaburbura sai idan wani uzuri ya auku wanda zai hana yin haka, kamar mutumin da zai mutu a cikin jirgin ruwa, kuma ya zamanto barin sa zai sa gawarsa ta ruɓe kafin a isa tashar tsayawar jirgin ruwa, to za a iya jefa gawar cikin ruwa bayan an ɗaura mata wani abu mai nauyi da zai sanya ta ta nutse a cikin ruwa.

Suratul Mursalat (16-28)
أَلَمۡ نُهۡلِكِ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٦ ثُمَّ نُتۡبِعُهُمُ ٱلۡأٓخِرِينَ ١٧ كَذَٰلِكَ نَفۡعَلُ بِٱلۡمُجۡرِمِينَ ١٨ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ١٩ أَلَمۡ نَخۡلُقكُّم مِّن مَّآءٖ مَّهِينٖ ٢٠ فَجَعَلۡنَٰهُ
فِي قَرَارٖ مَّكِينٍ ٢١ إِلَىٰ قَدَرٖ مَّعۡلُومٖ ٢٢ فَقَدَرۡنَا فَنِعۡمَ ٱلۡقَٰدِرُونَ ٢٣ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٢٤ أَلَمۡ نَجۡعَلِ ٱلۡأَرۡضَ كِفَاتًا ٢٥ أَحۡيَآءٗ وَأَمۡوَٰتٗا ٢٦
وَجَعَلۡنَا فِيهَا رَوَٰسِيَ شَٰمِخَٰتٖ وَأَسۡقَيۡنَٰكُم مَّآءٗ فُرَاتٗا ٢٧ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ٢٨

16. Yanzu ba Mu hallakar da na farko ba?

17. Sannan Muka biyo su da na ƙarshe?

18. Kamar haka Muke yi wa masu manyan laifuka.

19. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

20. Yanzu ba Mu halicce ku daga wani wulaƙantaccen ruwa ba?

21. Sannan Muka sanya shi cikin matabbata mai aminci?

22. Zuwa wani lokaci sananne?

23. Sannan Muka ƙaddara (komai ta yadda ya dace)? To madalla da Masu ƙaddarawa.

24. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

25. Yanzu ba Mu sanya ƙasa (ta zama) matattara ba?

26. (Ga) rayayyu da matattu?

27. Muka kuma sanya kafaffun duwatsu dogaye a cikinta, Muka kuma shayar da ku ruwa mai daɗi?

28. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tsoratar da kafirai cewa, shi ne ya hallaka al'ummun farko waɗanda suka kafirce masa, suka ƙaryata manzanninsa, sannan ya hallaka na bayansu waɗanda su ma suka ƙaryata manzanninsa, sannan ya yi alƙawarin cewa, kamar yadda ya hallaka waɗancan masu ƙaryatawar hakanan zai hallaka kafirai masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da abin da ya zo da shi na gaskiya. Sai ya bayyana cewa, halaka da tsananin azaba sun tabbata ga masu ƙaryatawa a ranar alƙiyama.
Sannan Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana ni'imar halitta da ya yi wa ɗan'adam mai nuna cikakkiyar Kudurarsa. Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tambayi bayinsa cewa, shin ba shi ne ya halicce su daga wani wulaƙantaccen ruwa ba, watau maniyyi? Ya ajiye wannan maniyyin a cikin wani wuri mai aminci, watau mahaifar 'ya mace, har zuwa wani sanannen lokaci, watau tsawon lokacin zaman jariri a cikin mahaifiyarsa wata tara ko ƙasa da haka. Sannan Allah ya ƙaddara siffar wannan abin haihuwa da matsayinsa da kamanninsa da sauran yanayin halittarsa. To madalla da masu ƙaddara komai yadda ya dace, shi ne Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**). Sai Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya sake tabbatar da cewa, tsananin azaba ya tabbata ga masu ƙaryatawa a ranar alƙiyama.
Sai Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya sake jawo hankalin mutane zuwa ga wata ni'imar da ya yi musu inda ya tambaye su cewa, shin ba shi ne ya sanya ƙasa ta zama mai tattara mutane gaba ɗaya ba; masu rai a cikin gidajensu a bayanta, matattu kuma a binne a cikin ƙaburburansu a ƙarƙashinta? Ya kuma sanya kafaffun duwatsu masu tsawo a cikinta waɗanda suke hana ta yin tangal-tangal, ya kuma shayar da mutane ruwa mai daɗi? To duk wanda yake da ikon yin wannan halittar, lalle sake tayar da matattu ba zai gagare shi ba. Don haka ya sake tabbatar da cewa, tsananin azaba ya tabbata ga masu ƙaryata waɗannan ni'imomin nasa a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Nuna wa kafirai cewa, idan a nan duniya sun ƙi bin umarnin Allah zuwa ga rahamarsa, to a ranar alƙiyama za a umarce su da su tafi zuwa ga azabarsa kuma dole ne su bi wannan umarnin.

2. Siffanta inuwar ‘yan wuta wadda babu wani sanyi ko kaɗan a cikinta ba ta kuma kare su daga zafin wutar Jahannama, watau dai babu wani hutu ko alheri a tare da ita.

3. Ranar alƙiyama zango-zango ce, a wani zangon ba za a bai wa ‘yan wuta damar yin wata magana ba ko su kawo wani hanzarinsu, a wani zangon kuma za a tambaye su za kuma su yi magana don su amsa tambayoyin da ake yi musu, har su riƙa faɗar uzurori na ƙarya.

4. A ranar alƙiyama Allah zai tattara dukkan bayinsa a wani makeken fili guda ɗaya don yin hukunci a tsakaninsu.

Suratul Mursalat (29-40)

ٱنطَلِقُوٓاْ إِلَىٰ مَا كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ﴿٢٩﴾ ٱنطَلِقُوٓاْ إِلَىٰ ظِلّٖ ذِي ثَلَٰثِ شُعَبٖ ﴿٣٠﴾ لَّا ظَلِيلٖ وَلَا يُغۡنِي مِنَ ٱللَّهَبِ ﴿٣١﴾ إِنَّهَا تَرۡمِي بِشَرَرٖ كَٱلۡقَصۡرِ ﴿٣٢﴾
كَأَنَّهُۥ جِمَٰلَتٞ صُفۡرٞ ﴿٣٣﴾ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ﴿٣٤﴾ هَٰذَا يَوۡمُ لَا يَنطِقُونَ ﴿٣٥﴾ وَلَا يُؤۡذَنُ لَهُمۡ فَيَعۡتَذِرُونَ ﴿٣٦﴾ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ﴿٣٧﴾ هَٰذَا يَوۡمُ
ٱلۡفَصۡلِۖ جَمَعۡنَٰكُمۡ وَٱلۡأَوَّلِينَ ﴿٣٨﴾ فَإِن كَانَ لَكُمۡ كَيۡدٞ فَكِيدُونِ ﴿٣٩﴾ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ﴿٤٠﴾

29. Ku tafi zuwa ga abin da kuka kasance kuna ƙaryatawa.

30. Ku tafi zuwa wata inuwa mai rassa uku.

31. Ba mai ba da inuwa ba kuma ba mai karewa daga harshen wuta ba.

32. Haƙiƙa ita tana jefa tartsatsi kamar ƙaton gini.

33. Kai ka ce su raƙuma ne baƙaƙe.

34. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

35. Wannan ita ce ranar da ba sa magana.

36. Kuma ba za a yi musu izini ba balle su kawo hanzari.

37. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

38. Wannan ita ce rana ta yin hukunci da Muka tara ku da na farko.

39. To idan kuna da wani tanadi na makirci sai ku ƙulla Mini.

40. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

A waɗannan ayoyi, bayan Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka)** ya tabbatar wa kafirai gaskiyar zuwan ranar alƙiyama, sai kuma ya bayyana musu irin mummunar azabar da za su gamu da ita matuƙar ba su yi imani ba. Rana ce wadda mala’iku masu tsaron Jahannama za su gargaɗa su su ce musu, su tafi zuwa ga azabar da suka kasance suna ƙaryatawa, su tafi zuwa wata inuwa ta hayaƙin wuta mai rassa uku: Inuwa ce wadda ba ta da sanyi irin na inuwa, ba ta kuma kare mutum daga harshen wuta da zafinta. Sannan ya siffanta wannan wutar da cewa, lalle ita wuta ce wadda take jefo tartsatsinta, kowane tartsatsi girmansa

kamar wani katafaren gini ne, sannan ga shi baƙi wuluk kamar baƙaƙen raƙuma. Don haka duk masu ƙaryatawa su sani cewa, tsananin azaba a ranar lahira ya tabbata a gare su.
Sannan Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana musu siffar wannan rana da cewa, rana ce da ba za a bar su su yi wata magana ba, kuma ba za a ba su izini su faɗi wani hanzarinsu ba a gaban Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) game da kafircinsu da laifukan da suka aikata. Don haka tsananin azaba ya tabbata a wannan rana ga masu ƙaryata labaran wannan rana ta alƙiyama.
Sai kuma Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya sanar da kafirai cewa, wannan fa ita ce ranar alƙiyama, kuma ga shi duk ya tattara su a cikinta su da sauran al'ummun da suka gabata a farfajiya ɗaya. Don haka idan suna da wani tanadi na makirci da suka shirya na yadda za su kuɓuce wa azabar wannan rana, to ga fili ga mai doki sai su nuna shi. Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya daɗa tabbatar musu cewa, tsananin azaba ya tabbata ga masu ƙaryata ranar yin hukunci a tsakaninsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Abin da yake shigar da bayi Aljanna bayan rahamar Allah, shi ne taƙawa, watau bin dokokin Allah da kyautatawa.

2. Inuwar 'yan Aljanna ba irin ta 'yan wuta ce ba, inuwarsu mai sanyi ce kuma ga 'ya'yan itatuwa na marmari, ga marmaro na ruwan daɗi mai gudana.

3. Kafirai ba su da wata rayuwa ta morewa sai wannan rayuwar ta duniya 'yar taƙaitacciya, daga nan sai a ingiza su zuwa azaba ta har abada.

4. Kafirai a lahira za a kama su da laifukan bijire wa ibadu, kamar salla da suka ƙi yi.

5. Girman sha'anin salla, ganin yadda aka ambace ta ita kaɗai duk da cewa ba ita kaɗai ce ibadar da suka ƙi yi ba, saboda bambancin Musulmi da kafiri shi ne tsayar da salla.

6. Alƙur'ani zance ne da ya fi kowane zance kyan bayani da kawo ƙwararan hujjoji da wa'azuzzuka masu ratsa zukata da bayanin hukunce-hukuncen shari'a da sakamakon masu biyayya ga Allah da waɗanda suka bijire masa, don haka babu wata shiriya bayan ta Alƙur'ani, babu kuma wani bayani da ya kai nasa.

Suratul Mursalat (41-50)
إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي ظِلَٰلٖ وَعُيُونٖ ۝٤١ وَفَوَٰكِهَ مِمَّا يَشۡتَهُونَ ۝٤٢ كُلُواْ وَٱشۡرَبُواْ هَنِيٓـَٔۢا بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ۝٤٣ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ۝٤٤ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ۝٤٥ كُلُواْ وَتَمَتَّعُواْ قَلِيلًا إِنَّكُم مُّجۡرِمُونَ ۝٤٦ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ۝٤٧ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱرۡكَعُواْ لَا يَرۡكَعُونَ ۝٤٨ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ۝٤٩ فَبِأَيِّ حَدِيثِۭ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ ۝٥٠

41. Lalle masu taƙawa suna cikin inuwoyi da idanuwan ruwa.

42. Da kuma ababan marmari daga abin da suke sha'awa.

43. Ku ci kuma ku sha kuna masu farin ciki saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa.

44. Lalle Mu kamar haka Muke saka wa masu kyautatawa.

45. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

46. Ku ci kuma ku ji daɗi kaɗan (a duniya), lalle ku kun tabbata manyan masu laifi.

47. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

48. Idan kuma aka ce da su: “Ku yi ruku'u”, to ba za su yi ruku'u ba.

49. Tsananin azaba ya tabbata a wannan ranar ga masu ƙaryatawa.

50. To da wane irin zance ne bayansa (Alƙur’ani) za su yi imani?

A waɗannan ayoyi kuma Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana kyakkyawan sakamakon masu taƙawa, watau waɗanda suka bi umarninsa suka kuma guje wa haninsa da cewa, za su sami shiga ƙarƙashin inuwoyin bishiyoyin Aljanna masu ni’ima, za su kuma sha daga idanuwan wani marmaro mai gudana mai matuƙar daɗi, za a kuma wadata su da kayan marmari irin duk wanda suke sha’awar su ci; mala’iku suna ce musu su ci daɗaɗan abin cikinta, su sha ruwanta mai daɗi saboda kyawawan ayyukan da suka aikata a duniya. Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya tabbatar da cewa, irin wannan sakamako da ya yi musu shi ne yake yi wa bayinsa masu kyautatawa. Don haka tsananin azaba ya tabbata ga masu ƙaryata abin da ya tanadar wa bayinsa masu taƙawa a wannan ranar.
Sai kuma Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya sake juyowa ga mushirikai, ya tsoratar da su da cewa, su ci su more rayuwar duniya na ɗan lokaci kaɗan, to amma su tabbata cewa, su masu manyan laifuka ne saboda kafirce wa Allah da ƙaryata manzanninsa da suka yi. Don haka tsananin azaba ya tabbata ga masu ƙaryatawa a ranar alƙiyama.
Sai kuma Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana mummunan taurin kansu a nan duniya lokacin da aka umarce su da su yi salla, suka ƙi yarda su yi, don haka tsananin azaba a wannan ranar ya tabbata ga masu ƙaryata abin da manzannin Allah suka zo da shi daga Allah.
Sannan Allah (**Mai tsarki da ɗaukaka**) ya bayyana cewa, idan har waɗannan kafiran sun guje wa Alƙur’ani da ya saukar mai cike da ɗimbin hikimomi da hujjoji kuma gagara-koyo, to da wane zance ne kuma za su yi imani? Lalle babu shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɗimuwar mushirikai game da Alƙur’ani, domin sun gaza siffanta shi da wata siffa ɗaya da za su ɓata shi da ita.

2. Alƙur’ani labari ne mai girma, saboda girman lamarinsa da zamantowarsa gagara-koyo, kuma maganar Allah.

3. Tsoratar da mushirikai mummunan sakamakon da yake jiran su idan ba su tuba ba.

4. Halittar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi a sama da ƙasa da kyautata abin da ya halitta, wani ƙwaƙƙwaran dalili ne mai nuna Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) game da tashi bayan mutuwa.

5. Bacci da daddare da samun damar hada-hada da rana, duka manyan ni’imomin Allah ne ga ɗan’adam waɗanda wajibi ne a kansa ya gode masa.

78-Suratun Naba’i

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Mafi shaharar sunayen wannan Sura shi ne ‘*Suratun Naba’i’*, saboda kalmar ‘*An-Naba’i’* ta zo a ayarta ta biyu. Ma’anar kalmar ita ce ‘Labari’.
A wasu littattafai kamar *Sahihul Bukhari* da *Tafsirin Ibn Aɗiyya da ‘Al-Kasshaf’* an kira ta da ‘Suratu Amma Yatasa’aluna’.
Tana da wasu sunaye daban ban da waɗannan.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* ba tare da wani saɓani ba.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin (80) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta sauka bayan ‘*Suratul Ma’arij’* kafin *‘Suratun Nazi’at*’.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta arba’in ne (40) a wurin mutanen Madina da Sham da Basra. Amma a wurin mutanen Makka da na Kufa adadinsu arba’in da ɗaya (41) ne.

5. Babban Jigonta:
Tana tabbatar da tashin alƙiyama da sakamako a bisa dalilai masu ƙarfi.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Bayanin shaci-faɗin mushirikai game da Alƙur’ani da abin da ya zo da shi na gaskiya wanda ya saɓa wa aƙidunsu, kamar rayuwa bayan mutuwa.
• Tsawatar wa mushirikai game da izgilin da suke yi wa Annabi (ﷺ) da Alƙur’ani.
• Kafa wa mushirikai ƙwaƙƙwarar hujja a kan yiwuwar tashi bayan mutuwa ta hanyar nuna musu cewa, Allah shi ne wanda ya halicci wasu manya-manyan halittu waɗanda sun fi halittar ɗan’adam girma nesa ba kusa ba, to ta ƙaƙa za a ce Allah ba zai iya dawo da matacce ba?
• Bayanin azabar da Allah zai yi wa kafirai a lahira da kuma kyakkyawan sakamakonsa ga muminai masu biyayya a gare shi.
• Ishara zuwa ga faffaɗan ilimin Allah wanda ya kewaye komai.

Suratun Naba’i (1-16)

عَمَّ يَتَسَآءَلُونَ ۝١ عَنِ ٱلنَّبَإِ ٱلۡعَظِيمِ ۝٢ ٱلَّذِي هُمۡ فِيهِ مُخۡتَلِفُونَ ۝٣ كَلَّا سَيَعۡلَمُونَ ۝٤ ثُمَّ كَلَّا سَيَعۡلَمُونَ ۝٥ أَلَمۡ نَجۡعَلِ ٱلۡأَرۡضَ مِهَٰدٗا ۝٦ وَٱلۡجِبَالَ أَوۡتَادٗا ۝٧ وَخَلَقۡنَٰكُمۡ أَزۡوَٰجٗا ۝٨ وَجَعَلۡنَا نَوۡمَكُمۡ سُبَاتٗا ۝٩ وَجَعَلۡنَا ٱلَّيۡلَ لِبَاسٗا ۝١٠ وَجَعَلۡنَا ٱلنَّهَارَ مَعَاشٗا ۝١١ وَبَنَيۡنَا فَوۡقَكُمۡ سَبۡعٗا شِدَادٗا ۝١٢ وَجَعَلۡنَا سِرَاجٗا وَهَّاجٗا ۝١٣ وَأَنزَلۡنَا مِنَ ٱلۡمُعۡصِرَٰتِ مَآءٗ ثَجَّاجٗا ۝١٤ لِّنُخۡرِجَ بِهِۦ حَبّٗا وَنَبَاتٗا ۝١٥ وَجَنَّٰتٍ أَلۡفَافًا ۝١٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Game da me suke tambayar junansu?

2. Game da labari ne mai girma.

3. Wanda game da shi ne suke saɓani

4. Ba haka ne ba, da sannu za su sani.

5. Sannan kuma tabbas, da sannu za su sani.

6. Yanzu ba mu sanya ƙasa shimfiɗa ba?

7. Duwatsu kuma turaku?

8. Muka kuma halicce ku bibbiyu (watau maza da mata)?

9. Muka kuma sanya baccinku (ya zama) hutu?

10. Muka kuma sanya dare (ya zama) sutura?

11. Muka kuma sanya yini don neman abinci?

12. Muka kuma gina (sammai) bakwai ƙarfafa a sama da ku?

13. Muka kuma sanya wata fitila mai tsananin haske (watau rana)?

14. Muka kuma saukar da ruwa mai kwarara daga (hadari) da ya batse da ruwa?

15. Domin Mu fitar da ƙwayoyi da tsirrai da shi?

16. Da kuma gonaki masu itatuwa sassarƙe da juna?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tambaya game da mushirikai masu ƙaryata Alƙur’ani cewa, game da mene ne suke yi wa juna tambaya bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aika musu Manzonsa (ﷺ)? Sai kuma ya bayyana kan abin da suke yi wa junansu tambaya da cewa, suna yin

tambaya ne game da labari mai girma, watau shi ne Alƙur'ani wanda Allah ya aiko Manzonsa (ﷺ) da shi kuma yake ƙunshe da maganar tashin alƙiyama domin yi wa kowa hisabi. Kafirai suna ta saɓani a kansa cewa, da me ya kamata su kwatanta shi, shin su kira shi da tsafi ko su ce masa waƙa ko bokanci, ko kuma su siffanta shi da tatsuniyoyin mutanen farko?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar musu da martani cewa, lamarin Alƙur'ani ba duk yadda suke faɗa ba ne, amma da sannu za su san mummunan ƙarshen ƙaryatawarsu gare shi, sannan hakan zai tabbata a gare su ba da jimawa ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalinsu ta hanyar tunatar da wasu ni'imominsa guda tara da ya yi musu waɗanda sun isa su zama ƙwararan hujjoji a kan ingancin manzancin Annabi (ﷺ) da gaskiyar tashin alƙiyama da Alƙur'ani yake faɗa musu.
Na farko, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye su cewa, ashe ba shi ne ya sanya musu ƙasa ta zama shimfiɗa a gare su ba, yadda suke rayuwa a kanta cikin nutsuwa? Lalle shi ne ya yi musu wannan ni'imar mai girma.
Na biyu, kuma ba shi ne ya kafa musu duwatsu a cikin ƙasa don su hana ta girgiza da tangal-tangal da su ba?
Na uku, ya kuma halicce su jinsin namiji da mace, don kowa ya sami nutsuwa da ɗan'uwansa da soyayya da tausayi da samun ƙaruwar zuriya?
Na huɗu, ya kuma sanya barcinsu ya zame musu hutu bayan sun gaji da ɗawainiya ta yau-da-gobe?
Na biyar, ya sanya musu dare ya zame musu sutura da zai lulluɓe su da duhunsa?
Na shida, ya kuma sanya musu rana lokaci ne da za su fita domin neman abincinsu da harkokinsu na rayuwa?
Na bakwai, ya kuma gina musu sammai bakwai masu ƙarfi a samansu?
Na takwas, ya sanya musu rana mai tsananin haske da suke amfana da haskenta da zafinta?
Na tara, ya saukar musu da ruwan sama mai matuƙar yawa daga gizagizai masu tatso ruwa daga cikinsu, domin ya fitar musu da dangogin ƙwaya da dangogin tsirrai da wannan ruwan? Ya kuma fitar musu da gonaki masu cike da itatuwa sassarƙafe da juna saboda yawansu? Lalle Allah ne ya yi musu duk waɗannan ni'imomin. To don me suke jayayya da abin da ya aiko Annabinsa (ﷺ) da shi, watau Alƙur'ani har suke ƙaryata rayuwa bayan mutuwa?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da zuwan ranar lahira babu makawa.

2. Da zarar an busa ƙaho busa ta biyu, to duk matattu za su firfito daga cikin ƙaburburansu don zuwa wajen hisabi ƙungiya-ƙungiya ba tare da wani ɓata lokaci ba.

3. A ƙarshen duniya duk tsarin gudanar da ita zai ruguje ne, wannan kuwa alama ce ta cewa duniya ta zo ƙarshe, alƙiyama kuma ta tsaya.

4. Ɗagawa da ƙetare iyakokin Allah su ne musabbabin shigar kafirai wutar Jahannama.

5. Cikar adalcin Allah wanda ya hukunta kafirai da sakamakon da ya dace da ayyukansu, bai zalunce su da komai ba.

6. Za a ninninka wa kafirai azabar wutar Jahannama. Wannan ayar ta 30, ita ce mafi tsananin ayar narko ga kafirai.

Suratun Naba’i (17-30)

إِنَّ يَوْمَ ٱلْفَصْلِ كَانَ مِيقَٰتًا ﴿١٧﴾ يَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ فَتَأْتُونَ أَفْوَاجًا ﴿١٨﴾ وَفُتِحَتِ ٱلسَّمَآءُ فَكَانَتْ أَبْوَٰبًا ﴿١٩﴾ وَسُيِّرَتِ ٱلْجِبَالُ فَكَانَتْ سَرَابًا ﴿٢٠﴾ إِنَّ جَهَنَّمَ كَانَتْ مِرْصَادًا ﴿٢١﴾ لِّلطَّٰغِينَ مَـَٔابًا ﴿٢٢﴾ لَّٰبِثِينَ فِيهَآ أَحْقَابًا ﴿٢٣﴾ لَّا يَذُوقُونَ فِيهَا بَرْدًا وَلَا شَرَابًا ﴿٢٤﴾ إِلَّا حَمِيمًا وَغَسَّاقًا ﴿٢٥﴾ جَزَآءً وِفَاقًا ﴿٢٦﴾ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ لَا يَرْجُونَ حِسَابًا ﴿٢٧﴾ وَكَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا كِذَّابًا ﴿٢٨﴾ وَكُلَّ شَىْءٍ أَحْصَيْنَٰهُ كِتَٰبًا ﴿٢٩﴾ فَذُوقُوا۟ فَلَن نَّزِيدَكُمْ إِلَّا عَذَابًا ﴿٣٠﴾

17. Lalle ranar hukunci ta kasance (rana ce) mai tsayayyen lokaci.

18. Ranar da za a busa ƙaho sai ku zo jama’a-jama’a.

19. Aka kuma buɗe sama sai ta zama ƙofofi.

20. Aka kuma tafiyar da duwatsu sai suka zama kawalwalniya.

21. Lalle Jahannama ta kasance madakata ce.

22. Makoma ce ga masu ɗagawa.

23. Masu zama ne a cikinta shekaru aru-aru.

24. Ba sa ɗanɗanar wani sanyi a cikinta ko wani abin sha.

25. Sai tafasasshen ruwa da ruwan mugunya.

26. Don sakayya da ta dace.

27. Lalle su sun kasance ba sa tsoron hisabi.

28. Suka kuma ƙaryata ayoyinmu iyakar ƙaryatawa.

29. Kuma kowane abu Mun ƙididdige shi a rubuce.

30. (Sai a ce da su): To ku ɗanɗana, don ba za Mu ƙara muku ba sai dai wata azaba.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, alƙiyama lokaci ne na tashin matattu, kuma rana ce mai ƙayyadajjen lokaci, don haka tana nan tafe ba makawa, a cikinta ne Allah zai yi hukunci tsakanin halittu gaba ɗaya. Rana ce da mala’ika zai yi busa ta biyu a cikin ƙaho, daga nan duk mutane za su fito ƙwansu da ƙwarƙwatarsu daga cikin ƙaburburansu ƙungiya-ƙungiya.
A ranar za a buɗe rufin sama ta zama mai buɗaɗɗun ƙofofi, inda mala’iku za su yi ta sauka da umarnin Allah. An kuma dandaƙe duwatsu sun bi iska kamar ƙura, sun koma tamkar kawalwalniya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan sakamakon masu ƙaryata gaskiya a wannan ranar, lokacin da Jahannama ce za ta zama makoma ga masu ɗagawa, masu wuce iyakokin Allah. Idan an jefa su a cikinta za su yi ta zama cikinta shekaru aru-aru har abada babu ranar fita. Su yi rayuwa ta azaba

da ƙunci a cikinta, domin kuwa ba za su taɓa shaƙar wata iska mai sanyi ba a cikinta, ba kuma za su sha wani daddaɗan abin sha ba, sai dai wani tafasasshen ruwa da mugunyar ‘yan wuta mai matsanancin wari. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan mummunan sakamako da ya yi musu shi ne sakayyar da ta dace da su, saboda kafircinsu da ɓatansu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin da ya ja suka cancanci wannan matsananciyar azabar da cewa, lalle sun kasance a duniya ba sa tsoron hisabin Allah a lahira, domin ba su yi imani da tashi bayan mutuwa ba, saboda da a ce suna jin tsoron ranar lahira da sun yi imani da ita, sun kuma yi ayyuka nagari. Kuma suka ƙaryata ayoyin da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) iya ƙaryatawa, ba su san cewa, Allah ya ƙididdige duk ayyukansu a rubuce a cikin littattafan ayyukansu ba? Don haka bayan an jefa su wutar Jahannama sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce musu su ɗanɗani azaba ta dindindin, babu abin da za a ƙara musu sai azaba a kan azaba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Taƙawa dalili ne na shiga Aljanna.
2. An keɓe inabi da Ambato, domin nuna matsayinsa da falalarsa da yawansa.

3. ‘Yan matan Aljanna dukkansu tsarekun juna ne kuma masu ƙananan shekaru.

4. Kofunan giyar Aljanna koyaushe a cike suke da giya, kuma ba sa yankewa.

5. Gidan Aljanna babu wata yasasshiyar magana a cikinsa kuma ‘yan Aljanna ba sa ƙaryata juna.

Suratun Naba’i (31-36)

إِنَّ لِلْمُتَّقِينَ مَفَازًا ﴿٣١﴾ حَدَآئِقَ وَأَعْنَٰبًا ﴿٣٢﴾ وَكَوَاعِبَ أَتْرَابًا ﴿٣٣﴾ وَكَأْسًا دِهَاقًا ﴿٣٤﴾ لَّا يَسْمَعُونَ فِيهَا لَغْوًا وَلَا كِذَّٰبًا ﴿٣٥﴾ جَزَآءً مِّن رَّبِّكَ عَطَآءً حِسَابًا ﴿٣٦﴾

31. Lalle masu taƙawa suna da babban rabo.

32. (Su ne) gonaki da inabai.

33. Da ‘yan mata tsaraiku.

34. Da kofin giya cikakke.

35. Ba sa jin maganar banza a cikinta ko kuma ƙarya.

36. Sakamako ne daga Ubangijinka, kyauta ce a lissafe (gwargwadon aikin kowa) .

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kyakkyawan sakamako na masu taƙawa, watau waɗanda suke bin umarnin Allah, suke kuma guje wa haninsa, inda ya tabbatar da cewa, suna da babban rabo, watau gidan Aljanna da samun kuɓuta daga shiga wuta.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu tanadin gonaki masu cike da dangogin kayan itatuwan marmari iri-iri da inabai mai yawa. Suna da kuma ‘yan mata tsareku a shekarunsu ga kuma cikakkun kofunan giya mai daɗin kwankwaɗa. Kuma ‘yan Aljanna a cikinta ba sa jin wata magana ta banza ko ta ƙarya, kuma sashinsu ba ya ƙaryata sashi.

Duk wannan sakamako da ya ba su kyauta ce isasshiya, kuma a lissafe kowa gwargwadon aikinsa nagari.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ranar alƙiyama babu mai iya yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) magana sai wanda aka ba wa izinin yin haka.

2. Babu mai ceto a lahira; mala'ika ne ko wani annabi ko salihi sai da izinin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hore wa duk wani ɗan'adam ya zaɓi hanyar da zai bi mai kyau ce ko marar kyau, don haka duk abin da ya same shi shi ya zaɓa wa kansa, ba a zalunce shi da komai ba.

4. Kusantowar ranar alƙiyama.

Suratun Naba'i (37-40)
رَّبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا ٱلرَّحۡمَٰنِۖ لَا يَمۡلِكُونَ مِنۡهُ خِطَابٗا ٣٧ يَوۡمَ يَقُومُ ٱلرُّوحُ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ صَفّٗاۖ لَّا يَتَكَلَّمُونَ إِلَّا مَنۡ أَذِنَ لَهُ ٱلرَّحۡمَٰنُ وَقَالَ صَوَابٗا ٣٨ ذَٰلِكَ ٱلۡيَوۡمُ ٱلۡحَقُّۖ فَمَن شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ مَـَٔابًا ٣٩ إِنَّآ أَنذَرۡنَٰكُمۡ عَذَابٗا قَرِيبٗا يَوۡمَ يَنظُرُ ٱلۡمَرۡءُ مَا قَدَّمَتۡ يَدَاهُ وَيَقُولُ ٱلۡكَافِرُ يَٰلَيۡتَنِي كُنتُ تُرَٰبَۢا ٤٠

37. Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu (watau Allah) Mai rahama; (halittu) ba sa samun ikon yi masa magana daga gare Shi.

38. Ranar da Jibrilu da mala'iku za su tsaya sahu-sahu; (halittu) ba sa iya magana sai fa wanda (Allah) Mai rahama Ya yi wa izini, ya kuma faɗi abin da ya dace.

39. Wannan rana ce tabbatacciya; saboda haka wanda ya ga dama sai ya riƙi kyakkyawar makoma zuwa ga Ubangijinsa.

40. Lalle Mun yi muku gargaɗin azaba ta kurkusa, a ranar da mutum zai ga abin da hannayensa suka gabatar (na alheri ko na sharri), kafiri kuma ya riƙa cewa: "Ina ma da na zama turɓaya!"

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana kansa da cewa, shi ne wanda ya yi wa masu taƙawa sakamakon da aka ambata, shi ne Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, mai rahama ga kowa a duniya mai jin ƙan muminai kaɗai a lahira, wanda duk halittu ba su mallaki ikon yi masa wata magana ba har sai ya yi izini.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a ranar ne Mala'ika Jibrilu da sauran mala'iku za su tsaya sahu-sahu, babu mai iya buɗe baki ya ceci wani sai wanda Allah mai rahama ya yi masa izinin ya yi ceto, ya kuma faɗi magana ta daidai, watau kalmar Tauhidi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, wannan ranar da ya yi bayanin siffofinta rana ce tabbatacciya sai ta auku babu makawa, don haka duk wanda ya so ya tsira a wannan ranar daga azabar Allah, to ya kama kyakkyawar hanyar da za ta sada shi da haka, watau yin ayyuka nagari da barin munana.

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da kafirai ya tabbatar musu cewa, lalle ya gargaɗe su da wata azaba ta kurkusa, ranar da mutum zai ga aikin da ya yi a duniya, kafiri kuma ya riƙa burin ina ma ya zama turɓaya, kamar sauran dabbobi da za a ce musu su zama turɓaya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Karɓar rayukan kafirai cikin tsanani da wahala da karɓar rayukan muminai cikin sauƙi da tausasawa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yin rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittunsa. Amma bai halatta wani ya yi rantsuwa ba da Allah ba.

3. Mala'ikun Allah suna da ayyuka daban-daban da aka ɗora musu, kuma kowane yana yin aikinsa kamar yadda aka umarce shi ba tare da saɓawa ba.

4. Rantsuwa da mala'iku yana nuna cikar miƙa wuyansu ga Allah da gaggawar cika umarninsa.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai tashi dukkan halittu da busa ɗaya da mala'ika zai yi a ƙaho.

6. Duk wata halitta Allah zai fito da ita bayan ƙasa ne, domin hisabi a ranar alƙiyama.

79-Suratun Nazi’at

Mabuɗin Sura:

1.Sunanta:
An fi sanin wannan Sura da ‘*Suratun Nazi’at*’, watau da kalmar farko ta Surar. Amma a cikin Sahihul Bukhari da wasu littattafan tafsiri da dama an kira ta da ‘*Suratu Wan-Nazi’at*’.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya,* babu wani saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin da ɗaya (81) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta sauka bayan ‘*Suratun Naba’i*’ kafin *‘Suratul Infiɗar*’.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta arba’in da shida ne (46) a lissafin mutanen Kufa. Amma a wurin malaman sauran garuruwa adadinsu arba’in da biyar ne (45).

5. Babban Jigonta:
Tsoratar da masu ƙaryata ranar alƙiyama ta hanyar bayanin mutuwa da ambaton sakamakon ranar alƙiyama.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tabbatar da tashi bayan mutuwa da sakamako da kuma rushe aƙidar mushirikai a kan haka.
• Bayanin abubuwan ban tsoro na ranar alƙiyama.
• Rushe aƙidar mushirikai ta cewa, ba zai yiwu a sake tashin matattu ba bayan sun zama ƙasusuwa rududdugaggu.
• Nuna cewa mushirikai suna ƙaryata ranar alƙiyama ne saboda ɗagawarsu wadda za ta kai su ta baro, kamar yadda ta kai Fir’auna ta baro.
• Kafa ƙwaƙƙwarar hujja a kan yiwuwar tashin matattu wadda ita ce halittar sammai da ƙasa mai nuna cikar Kudurar Allah a kan komai.
• Tabbatar da cewa, babu wanda ya san lokacin tashin alƙiyama sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratun Nazi’at (1-14)

وَٱلنَّٰزِعَٰتِ غَرۡقٗا ١ وَٱلنَّٰشِطَٰتِ نَشۡطٗا ٢ وَٱلسَّٰبِحَٰتِ سَبۡحٗا ٣ فَٱلسَّٰبِقَٰتِ سَبۡقٗا ٤ فَٱلۡمُدَبِّرَٰتِ أَمۡرٗا ٥ يَوۡمَ تَرۡجُفُ ٱلرَّاجِفَةُ ٦ تَتۡبَعُهَا ٱلرَّادِفَةُ ٧ قُلُوبٞ يَوۡمَئِذٖ وَاجِفَةٌ ٨ أَبۡصَٰرُهَا خَٰشِعَةٞ ٩ يَقُولُونَ أَءِنَّا لَمَرۡدُودُونَ فِي ٱلۡحَافِرَةِ ١٠ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمٗا نَّخِرَةٗ ١١ قَالُواْ تِلۡكَ إِذٗا كَرَّةٌ خَاسِرَةٞ ١٢ فَإِنَّمَا هِيَ زَجۡرَةٞ وَٰحِدَةٞ ١٣ فَإِذَا هُم بِٱلسَّاهِرَةِ ١٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da (mala'iku) masu cizgar (ran kafiri) mummunar cizga.

2. Da kuma (mala'iku) masu zare (ran mumini) sassauƙar zarewa.

3. Da kuma (mala'iku) masu ninƙaya (a sama don sauko da umarni) ninƙaya mai tsananin sauri.

4. Sannan da (mala'iku) masu matuƙar rigegeniya (don zartar da umarnin Allah).

5. Sannan da (mala'iku) masu tsara al'amura.

6. Ranar da mai girgizawa za ta yi girgiza (watau busar ƙaho ta farko).

7. Mai bin ta kuma za ta biyo ta (watau busa ta biyu).

8. Wasu zukata a wannan ranar a tsorace suke.

9. Idanuwansu kuma a ƙasƙance suke.

10. (A duniya) suna cewa: "Yanzu zai yiwu a dawo da mu a raye (bayan mutuwa)?

11. "Yanzu ko bayan mun zama ƙasusuwa rududdugaggu?"

12. Suka ce: "Idan ko ya yiwu, to wannan komawa ce mai cike da asara."

13. To lalle ita kawai tsawa ce guda ɗaya tal!.

14. Sai ga su a bayan ƙasa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantse-rantse guda biyar. Ya rantse da mala'iku masu fizgar rayukan kafirai mummunar fizga yayin da suka zo mutuwa. Ya kuma yi rantsuwa da mala'iku masu zare rayukan muminai cikin sauƙi yayin mutuwarsu. Ya kuma rantse da mala'iku masu ninƙaya daga sama zuwa ƙasa ɗauke da umarnin Allah. Ya kuma yi rantsuwa da mala'iku masu rigegeniya da junansu wajen zartar da umarnin Allah. Ya kuma yi rantsuwa da mala'iku masu zartar da al'amuran da ya tsara ko ya hukunta a cikin bayinsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wadannan rantse-rantse ne domin ya tabbatar wa mushirikai cewa lalle za a tashe su bayan mutuwarsu domin yi musu hisabi da sakamako.
Sai kuma Allah ya bayyana ranar alƙiyama da cewa, ita ce ranar da ƙasa za ta girgiza lokacin busar ƙaho ta farko, sannan busa ta biyu ta biyo bayanta. A wannan ranar zukatan wasu mutane za su cika da tsoro,

alamun ƙasƙanci da wulaƙanci su bayyana a idanuwansu. Su ne kuma a duniya cikin izgili da fitsara suke cewa, wai shin bayan sun mutu anya za a sake dawo da su wata rayuwa sabuwa, bayan sun zama rududdugaggun ƙasusuwa rarakakku? Wai ta yaya kuma za a ce za a dawo musu da rayukansu? Wai da kuwa haka zai faru da ya zame musu dawowa mai cike da asara.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, wannan sassauƙan al'amari ne a wurinsa, domin kuwa sake dawo musu da rayukansu al'amari ne na tsawa guda ɗaya tal wadda mala'ika mai busa ƙaho zai yi, sai kawai kowa da kowa ya fito da ransa a bayan ƙasa bayan a da yana matacce a cikinta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar wa da Allah yin magana da sauti da harafi wadda ake ji, kamar yadda ya dace da girmansa.

2. Muhimmancin sassauta kalamai wajen kira zuwa ga Allah, ko da kuwa ga mutumin da kafircinsa ya kai irin na Fir'auna.

3. Mai tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai amfana da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da wa'azuzzukansa, don haka ganin yadda aka yi wa Fir'auna zai sa shi ya fahimci cewa, duk wani ma wanda zai yi ɗagawa da girman kai irin na Fir'auna shi ma zai gamu da sakamako irin na Fir'auna.

4. Nuna wa mushirikai cewa, lalle su ma su shiga taitayinsu game da ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da suke yi saboda ba su fi ƙarfin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya damƙe su da uƙubarsa ba irin yadda ya damƙi Fir'auna da jama'arsa.

5. Lallashin Annabi (ﷺ) game da ɗagawar mushirikai da nuna masa cewa ba shi ne farau ba, haka ya faru ga annabawan Allah kamar Annabi Musa, amma daga ƙarshe Allah ya ba shi galaba, don haka shi ma zai yi galaba a kan mutanensa masu ƙaryata shi.

Suratun Nazi'at (15-26)
هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰٓ ١٥ إِذۡ نَادَىٰهُ رَبُّهُۥ بِٱلۡوَادِ ٱلۡمُقَدَّسِ طُوٗى ١٦ ٱذۡهَبۡ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ١٧ فَقُلۡ هَل لَّكَ إِلَىٰٓ أَن تَزَكَّىٰ ١٨ وَأَهۡدِيَكَ إِلَىٰ رَبِّكَ فَتَخۡشَىٰ ١٩ فَأَرَىٰهُ ٱلۡأٓيَةَ ٱلۡكُبۡرَىٰ ٢٠ فَكَذَّبَ وَعَصَىٰ ٢١ ثُمَّ أَدۡبَرَ يَسۡعَىٰ ٢٢ فَحَشَرَ فَنَادَىٰ ٢٣ فَقَالَ أَنَا۠ رَبُّكُمُ ٱلۡأَعۡلَىٰ ٢٤ فَأَخَذَهُ ٱللَّهُ نَكَالَ ٱلۡأٓخِرَةِ وَٱلۡأُولَىٰٓ ٢٥ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّمَن يَخۡشَىٰٓ ٢٦

15. Shin labarin Musa ya zo maka?

16. Lokacin da Ubangijinsa Ya kirawo shi a kwari mai tsarki, (watau) Ɗuwa?

17. (Aka ce da shi): Ka tafi zuwa ga Fir'auna, haƙiƙa shi ya yi ɗagawa.

18. Sai ka ce: "Shin zai yiwu gare ka kuwa ka tsarkaka?
19. "In kuma shiryar da kai zuwa ga Ubangijinka, sai ka ji tsoron Sa?

20. Sai ya nuna masa babbar aya.

21. Sai ya ƙaryata ya kuma kangare.

22. Sannan ya ba da baya yana ta gaggawa.

23. Sai ya tattara (jamaʾarsa) sai ya yi shela.

24. Sai ya ce, "Ni ne ubangijinku mafi girma!"

25. Saboda haka Allah Ya kama shi da azabar lahira (watau Jahannama) da ta duniya (watau nutse wa a ruwa).

26. Lalle a game da wannan tabbas akwai izina ga wanda yake tsoron (Allah).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa (ﷺ) labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da ya aike shi zuwa ga Firʾauna da jamaʾarsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, shin labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo masa tare da babban maƙiyinsa Firʾauna lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo shi ya yi magana da shi a kwarin *Ɗuwa* mai tsarki? Watau wani wuri ne kusa Dutsen Ɗuri, inda Allah ya ba shi manzanci ya kuma umarce shi da ya tunkari Firʾauna Sarkin Misra, domin kuwa ya ƙetare duk wasu iyakokin Allah, ya kuma shimfiɗa mulki na zalunci a kan Banu Israʾila. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya yi wa Firʾauna tayin ko zai tsarkaka cikin tausasan kalmomi na hikima, ya yi watsi da aikata kafirci da zalunci ya musulunta, shi kuma Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiryar da shi zuwa sanin Ubangijinsa mahaliccinsa, don ya sami tsoronsa ya aikata abin da zai jawo masa yardarsa ya guji duk abin da zai sa ya yi fushi da shi. Amma sai Firʾauna ya bijire wa tayin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi masa.
Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) nan take ya nuna wa Firʾauna mafi girman ayoyinsa masu nuna lalle shi Manzon Allah ne, watau ya nuna masa hannunsa mai haske kamar fitila ba tare da wata cuta ba da kuma sandarsa mai rikiɗa ta zama macijiya. Amma Firʾauna bai yi wata-wata ba sai ya ƙaryata waɗannan ayoyin, ya bijire wa yin imani da gaskiyar da Annabi Musa ya zo masa da ita. Bai ma tsaya iya nan ba, sai da ya shiga tattara rundunoninsa don faɗa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya yi shela cikin jamaʾarsa da cewa, shi ne ubangijinsu mafi girma, don haka kada su yi wa kowa biyayya sai shi kaɗai.
Sai kuwa mutanen Firʾauna suka yarda suka bi shi a kan ɓatansa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya damƙe shi da uƙubar farko ta nan duniya ya nutsar da shi a cikin ruwa, da kuma uƙubar ƙarshe yayin da zai shigar da shi mafi tsananin azabar wuta a lahira.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a cikin irin wannan uƙuba da ya yi wa Firʾauna da mutanensa akwai izina da waʾazi ga wanda yake tsoron Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittar sama duk kuwa da girman da take da shi da ƙarfinta da ɗaukakarta, babban dalili ne mai nuna cikakkiyar Ƙudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta sake raya matattu.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shimfiɗa ƙasa ne bayan ya gama halittar sama, tare da cewa halittar ƙasa ta gabaci halittar sama, kamar yadda ya zo a cikin '*Suratul Baƙara'*, aya ta 29, da '*Suratu Fussilat'*, aya ta tara zuwa ta 11. Maʾanar shimfiɗa ƙasa kuwa shi ne abin da ya zo a aya ta 31 da 32 a wannan Surar.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ruwa da tsirrai da ya samar a bayan ƙasa don amfanin dabbobin mutane, domin duk abin da ya amfani dabbobinsu to su ya amfanar, domin dabbobinsu suna daga cikin kayan amfaninsu. Sai dai ambaton dabbobi a nan domin a yi nuni ne ga cewa, su ma suna

tarayya da ɗan'adam wajen amfanuwa da albarkatun ƙasa, to amma shi ɗan'adam ya kamata ya ɗara su a nan, watau ya ɗauki izina da wa'azi daga ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa a bayan ƙasa, kamar yadda ya zo a *'Suratu Ɗaha'*, aya ta 54.

Suratun Nazi'at (27-33)

ءَأَنتُمۡ أَشَدُّ خَلۡقًا أَمِ ٱلسَّمَآءُۚ بَنَىٰهَا ٢٧ رَفَعَ سَمۡكَهَا فَسَوَّىٰهَا ٢٨ وَأَغۡطَشَ لَيۡلَهَا وَأَخۡرَجَ ضُحَىٰهَا ٢٩ وَٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ دَحَىٰهَآ ٣٠ أَخۡرَجَ مِنۡهَا مَآءَهَا وَمَرۡعَىٰهَا ٣١ وَٱلۡجِبَالَ أَرۡسَىٰهَا ٣٢ مَتَٰعًا لَّكُمۡ وَلِأَنۡعَٰمِكُمۡ ٣٣

27. Yanzu ku ne halittarku ta fi tsanani ko kuwa sama wadda Shi ne Ya gina ta?

28. Ya ɗaukaka rufinta Ya kuma daidaita ta.

29. Ya lulluɓe darenta da duhu Ya kuma fitar da hasken hantsinta.

30. Ƙasa kuma bayan haka Ya shimfiɗa ta.

31. Ya fitar da ruwanta da makiyayarta daga gare ta.

32. Duwatsu kuma Ya kafa su.

33. Don jin daɗinku da na dabbobinku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kafa wa mushirikai masu ƙaryata tashin alƙiyama wata ƙaƙƙarfar hujja ta hankali, inda ya tambaye su cewa, wai shin halittarsu ce ta fi ba da wahala ko kuma halittar sama wadda Allah ne ya gina ta da cikar Ƙudurarsa? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗaukaka rufinta sama sannan ya daidaita ta babu wata ɓaraka ko tsagewa ko wani aibi a tare da ita. Sannan kuma idan rana ta faɗi sai ya sanya darenta ya yi duhu ko'ina a bayan ƙasa, kuma idan rana ta hudo da hantsi sai ko'ina ya yi haske. Kuma bayan ya gama halittar sama sai ya dawo ya shimfiɗa ƙasa ya sanya mata ababan amfaninta waɗanda suka haɗa da ruwa da ya fitar da idanuwansu masu kwarara a bayan ƙasa, ya fitar da tsirrai waɗanda dabbobi suke ci a wuraren kiwonsu. Duwatsu kuwa ya kafa su a cikinta, don kada ta riƙa tangal-tangal da na bayanta.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa mutane cewa, duk waɗannan ababan amfani ne gare su da dabbobinsu. Don haka wanda ya ƙagi irin waɗannan halittu, ai sake dawo musu da ransu bayan sun mutu ba abu ne da zai gagare shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin tsoron ranar tashin alƙiyama wanda ya kere kowane abin ban tsoro.

2. Abubuwan ban tsoro na ranar alƙiyama za su tunatar da mutum ayyukansa da ya yi a duniya, a lokacin zai yi burin daɗuwar kyawawan ayyukansa ko da daidai da ƙwayar komayya ne, zai kuma yi baƙin cikin ƙaruwar munanan ayyukansa ko da daidai da ƙwayar komayya ne.

3. Ɗagawa da ƙetare iyakokin Allah da fifita rayuwar duniya a kan ta lahira suna daga cikin dalilai masu sabbaba shiga wutar Jahannama.

4. Tsoron tsayuwa a gaban Allah ranar alƙiyama da nisantar bin son zuciya, sababi ne na shiga Aljanna.

Suratun Nazi'at (34-41)

مَتَٰعًا لَّكُمۡ وَلِأَنۡعَٰمِكُمۡ ﴿٣٣﴾ فَإِذَا جَآءَتِ ٱلطَّآمَّةُ ٱلۡكُبۡرَىٰ ﴿٣٤﴾ يَوۡمَ يَتَذَكَّرُ ٱلۡإِنسَٰنُ مَا سَعَىٰ ﴿٣٥﴾ وَبُرِّزَتِ ٱلۡجَحِيمُ لِمَن يَرَىٰ ﴿٣٦﴾ فَأَمَّا مَن طَغَىٰ ﴿٣٧﴾
وَءَاثَرَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ﴿٣٨﴾ فَإِنَّ ٱلۡجَحِيمَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ﴿٣٩﴾ وَأَمَّا مَنۡ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ وَنَهَى ٱلنَّفۡسَ عَنِ ٱلۡهَوَىٰ ﴿٤٠﴾ فَإِنَّ ٱلۡجَنَّةَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ﴿٤١﴾

34. Sannan idan mafi girman busar ƙaho ta zo (watau busa ta biyu).

35. A ranar da mutum zai tuna abin da ya aikata.

36. Aka kuma bayyana (wutar) Jahimu ga kowane mai gani.

37. To (a wannan ranar) duk wanda ya yi ɗagawa.

38. Ya kuma fifita rayuwar duniya.

39. To lalle (wutar) Jahimu ita ce makoma.

40. Duk wanda kuma ya ji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa, ya kuma hana zuciya bin abin da take so.

41. To lalle Aljanna ita ce makoma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi mushirikai masu ƙaryata tashin alƙiyama da su kiyayi ranar da za su yi nadama kuma nadamarsu ba za ta yi musu amfanin komai ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, idan har busar ƙaho ta biyu ta zo wadda tsoron da ke cikinta zai mamaye komai, to alƙiyama ta tsaya ke nan, kuma a ranar ne mutum zai tuna duk abin da ya aikata a duniya mai kyau da mummuna, a kuma bayyanar da wutar Jahannama a sarari don kowa ya gan ta tana jiran ta karɓi 'ya'yanta. A nan ne mutane za su kasu kashi biyu: Duk wanda ya ƙetare iyakokin Allah da kafirci da saɓo, ya kuma fifita rayuwar duniya mai ƙarewa a kan rayuwar lahira mai wanzuwa, to wannan wutar Jahannama ce makomarsa. Amma kuma wanda ya ji tsoron tsayuwa a gaban Ubangijinsa, ya hana ransa bin son zuciyarsa, to wannan Aljanna ce makomarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu wanda ya san lokacin zuwan ranar alƙiyama sai Allah shi kaɗai.

2. Mai amfana da gargaɗin Annabi (ﷺ) game da ranar alƙiyama shi ne wanda yake jin tsoron tsayuwa a gaban Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) don yi masa hisabi. Amma wanda bai yi imani da ranar lahira ba, to wannan ba zai amfana da duk wani gargaɗi da tsoratarwa da ake yi masa ba.

3. Rayuwar duniya ba a bakin komai take ba idan an kwatantata da ta lahira.

Suratun Nazi'at (42-46)
يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلسَّاعَةِ أَيَّانَ مُرْسَىٰهَا ﴿٤٢﴾ فِيمَ أَنتَ مِن ذِكْرَىٰهَآ ﴿٤٣﴾ إِلَىٰ رَبِّكَ مُنتَهَىٰهَآ ﴿٤٤﴾ إِنَّمَآ أَنتَ مُنذِرُ مَن يَخْشَىٰهَا ﴿٤٥﴾ كَأَنَّهُمْ يَوْمَ يَرَوْنَهَا لَمْ يَلْبَثُوٓاْ إِلَّا عَشِيَّةً أَوْ ضُحَىٰهَا ﴿٤٦﴾

42. Suna tambayar ka game da alƙiyama, yaushe ne lokacinta?

43. Me ya gama ka da ambaton lokacinta?

44. Zuwa ga Ubangijinka ne iyakacin saninta yake.

45. Kai dai kawai mai gargaɗin wanda yake tsoron ta ne.

46. Kai ka ce su ranar da za su gan ta ba su zauna ba (a duniya) face wani yammaci ko kuma hantsinta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda mushirikai masu ƙaryata zuwan ranar alƙiyama suka matsa wa Manzon Allah (ﷺ) da tambayar ƙwaƙwa game da takamaiman lokacin zuwanta da nufin su ƙure shi, ba wai don su gamsu su yi imani ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, babu abin da ya haɗa Manzonsa (ﷺ) da sanin takamaiman lokacin alƙiyama, domin ba wannan ne aikin da aka ɗora masa ba; ilimin sanin haka yana ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai bai kuma sanar da kowa shi ba. Shi Manzon Allah (ﷺ) aikinsa shi ne kawai ya gargaɗi duk wanda yake tsoron ranar tashin alƙiyama domin shi ne zai amfana da gargaɗinsa. Su kuwa mushirikai masu ƙaryata ta duk ranar da za su gan ta, za su ga kamar ma ba su rayu a duniya ba sai gwargwadon yini ɗaya kacal ko hantsin yini guda, watau farkonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cewa Annabi (ﷺ) mutum ne kamar sauran mutane, abin da yake bijiro musu na farin ciki ko baƙin ciki da nuna damuwa yana bijiro masa shi ma.

2. An bayyana lalurar Abdullahi ɗan Ummu Maktum (Allah ya kara masa yarda) ta makanta, don nuna uzurinsa na fuskanto Manzon Allah (ﷺ) da tambaya alhalin yana cikin wani zarafi, saboda rashin gani da yake fama da shi.

3. Sanin abin da yake cikin zukata aikin Allah ne shi kaɗai, don haka Manzon Allah (ﷺ) bai san wane ne zai tsarkaka ba wane ne kuma ba zai tsarkaka ba. Wannan shi ma uzuri ne ga Manzon Allah (ﷺ) game da mayar da hankali da ya yi ga shugabannin Ƙuraishawa ya ƙyale Ɗan Ummu Maktum (Allah ya kara masa yarda) don yana zaton za su musulunta.

4. Wadata da ni'ima ta duniya takan hana wasu amfana da wa'azi da faɗakarwa.

5. Abin da ya dace ya kuma fi zama wajibi ga mai wa'azi shi ne ya fi mayar da hankalinsa ga wanda ya kawo kansa gare shi yana mai nuna buƙatarsa, ba wanda wadatarsa ta hana shi ya nemi sani ko ya nuna buƙatarsa ga wani alheri ba. Rashin tsarkakarsa da amfanuwarsa da wa'azin mai wa'azi ba za ta cutar da

mai waʾazin da komai ba, domin wannan ba a hannunsa yake ba. Don haka ba a barin maslaha ta dahir a kama wadda ba ta wuce zato ba.

6. Tabbatar da cewa, Alƙurʾani daga Allah ne ba maganar Manzon Allah ba ce, domin mutum ba ya fitowa ya zargi kansa da kansa irin haka.

7. Falalar Abdullahi ɗan Ummu Maktum da kyakkyawar shaidar tsarkaka da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa.

79-Suratun Nazi’at

Mabuɗin Sura:

1.Sunanta:
An fi sanin wannan Sura da ‘*Suratun Nazi’at*’, watau da kalmar farko ta Surar. Amma a cikin Sahihul Bukhari da wasu littattafan tafsiri da dama an kira ta da ‘*Suratu Wan-Nazi’at*’.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya,* babu wani saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin da ɗaya (81) a jerin saukar surorin Alƙurʾani, ta sauka bayan ‘*Suratun Naba’i*’ kafin *‘Suratul Infiɗar*’.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta arba’in da shida ne (46) a lissafin mutanen Kufa. Amma a wurin malaman sauran garuruwa adadinsu arba’in da biyar ne (45).

5. Babban Jigonta:
Tsoratar da masu ƙaryata ranar alƙiyama ta hanyar bayanin mutuwa da ambaton sakamakon ranar alƙiyama.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tabbatar da tashi bayan mutuwa da sakamako da kuma rushe aƙidar mushirikai a kan haka.
• Bayanin abubuwan ban tsoro na ranar alƙiyama.
• Rushe aƙidar mushirikai ta cewa, ba zai yiwu a sake tashin matattu ba bayan sun zama ƙasusuwa rududdugaggu.
• Nuna cewa mushirikai suna ƙaryata ranar alƙiyama ne saboda ɗagawarsu wadda za ta kai su ta baro, kamar yadda ta kai Fir’auna ta baro.
• Kafa ƙwaƙƙwarar hujja a kan yiwuwar tashin matattu wadda ita ce halittar sammai da ƙasa mai nuna cikar Kudurar Allah a kan komai.

• Tabbatar da cewa, babu wanda ya san lokacin tashin alƙiyama sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratun Nazi'at (1-14)

وَٱلنَّٰزِعَٰتِ غَرۡقٗا ١ وَٱلنَّٰشِطَٰتِ نَشۡطٗا ٢ وَٱلسَّٰبِحَٰتِ سَبۡحٗا ٣ فَٱلسَّٰبِقَٰتِ سَبۡقٗا ٤ فَٱلۡمُدَبِّرَٰتِ أَمۡرٗا ٥ يَوۡمَ تَرۡجُفُ ٱلرَّاجِفَةُ ٦ تَتۡبَعُهَا ٱلرَّادِفَةُ ٧ قُلُوبٞ يَوۡمَئِذٖ وَاجِفَةٌ ٨ أَبۡصَٰرُهَا خَٰشِعَةٞ ٩ يَقُولُونَ أَءِنَّا لَمَرۡدُودُونَ فِي ٱلۡحَافِرَةِ ١٠ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمٗا نَّخِرَةٗ ١١ قَالُواْ تِلۡكَ إِذٗا كَرَّةٌ خَاسِرَةٞ ١٢ فَإِنَّمَا هِيَ زَجۡرَةٞ وَٰحِدَةٞ ١٣ فَإِذَا هُم بِٱلسَّاهِرَةِ ١٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da (mala'iku) masu cizgar (ran kafiri) mummunar cizga.

2. Da kuma (mala'iku) masu zare (ran mumini) sassauƙar zarewa.

3. Da kuma (mala'iku) masu ninƙaya (a sama don sauko da umarni) ninƙaya mai tsananin sauri.

4. Sannan da (mala'iku) masu matuƙar rigegeniya (don zartar da umarnin Allah).

5. Sannan da (mala'iku) masu tsara al'amura.

6. Ranar da mai girgizawa za ta yi girgiza (watau busar ƙaho ta farko).

7. Mai bin ta kuma za ta biyo ta (watau busa ta biyu).

8. Wasu zukata a wannan ranar a tsorace suke.

9. Idanuwansu kuma a ƙasƙance suke.

10. (A duniya) suna cewa: "Yanzu zai yiwu a dawo da mu a raye (bayan mutuwa)?

11. "Yanzu ko bayan mun zama ƙasusuwa rududdugaggu?"

12. Suka ce: "Idan ko ya yiwu, to wannan komawa ce mai cike da asara."

13. To lalle ita kawai tsawa ce guda ɗaya tal!.

14. Sai ga su a bayan ƙasa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantse-rantse guda biyar. Ya rantse da mala'iku masu fizgar rayukan kafirai mummunar fizga yayin da suka zo mutuwa. Ya kuma yi rantsuwa da mala'iku masu zare rayukan muminai cikin sauƙi yayin mutuwarsu. Ya kuma rantse da mala'iku masu ninƙaya daga sama zuwa ƙasa ɗauke da umarnin Allah. Ya kuma yi rantsuwa da mala'iku masu rigegeniya da junansu wajen zartar da umarnin Allah. Ya kuma yi rantsuwa da mala'iku masu zartar da al'amuran da ya tsara ko ya hukunta a cikin bayinsa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi waɗannan rantse-rantse ne domin ya tabbatar wa mushirikai cewa lalle za a tashe su bayan mutuwarsu domin yi musu hisabi da sakamako.
Sai kuma Allah ya bayyana ranar alƙiyama da cewa, ita ce ranar da ƙasa za ta girgiza lokacin busar ƙaho ta farko, sannan busa ta biyu ta biyo bayanta. A wannan ranar zukatan wasu mutane za su cika da tsoro, alamun ƙaskanci da wulaƙanci su bayyana a idanuwansu. Su ne kuma a duniya cikin izgili da fitsara suke cewa, wai shin bayan sun mutu anya za a sake dawo da su wata rayuwa sabuwa, bayan sun zama rududdugaggun ƙasusuwa rarakakku? Wai ta yaya kuma za a ce za a dawo musu da rayukansu? Wai da kuwa haka zai faru da ya zame musu dawowa mai cike da asara.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, wannan sassauƙan al'amari ne a wurinsa, domin kuwa sake dawo musu da rayukansu al'amari ne na tsawa guda ɗaya tal wadda mala'ika mai busa ƙaho zai yi, sai kawai kowa da kowa ya fito da ransa a bayan ƙasa bayan a da yana matacce a cikinta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar wa da Allah yin magana da sauti da harafi wadda ake ji, kamar yadda ya dace da girmansa.

2. Muhimmancin sassauta kalamai wajen kira zuwa ga Allah, ko da kuwa ga mutumin da kafircinsa ya kai irin na Fir'auna.

3. Mai tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai amfana da ayoyin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da wa'azuzzukansa, don haka ganin yadda aka yi wa Fir'auna zai sa shi ya fahimci cewa, duk wani ma wanda zai yi ɗagawa da girman kai irin na Fir'auna shi ma zai gamu da sakamako irin na Fir'auna.

4. Nuna wa mushirikai cewa, lalle su ma su shiga taitayinsu game da ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da suke yi saboda ba su fi ƙarfin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya damƙe su da uƙubarsa ba irin yadda ya damƙi Fir'auna da jama'arsa.

5. Lallashin Annabi (ﷺ) game da ɗagawar mushirikai da nuna masa cewa ba shi ne farau ba, haka ya faru ga annabawan Allah kamar Annabi Musa, amma daga ƙarshe Allah ya ba shi galaba, don haka shi ma zai yi galaba a kan mutanensa masu ƙaryata shi.

Suratun Nazi'at (15-26)
هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰٓ ١٥ إِذۡ نَادَىٰهُ رَبُّهُۥ بِٱلۡوَادِ ٱلۡمُقَدَّسِ طُوٗى ١٦ ٱذۡهَبۡ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ١٧ فَقُلۡ هَل لَّكَ إِلَىٰٓ أَن تَزَكَّىٰ ١٨ وَأَهۡدِيَكَ إِلَىٰ رَبِّكَ فَتَخۡشَىٰ ١٩ فَأَرَىٰهُ ٱلۡأٓيَةَ ٱلۡكُبۡرَىٰ ٢٠ فَكَذَّبَ وَعَصَىٰ ٢١ ثُمَّ أَدۡبَرَ يَسۡعَىٰ ٢٢ فَحَشَرَ فَنَادَىٰ ٢٣ فَقَالَ أَنَا۠ رَبُّكُمُ ٱلۡأَعۡلَىٰ ٢٤ فَأَخَذَهُ ٱللَّهُ نَكَالَ ٱلۡأٓخِرَةِ وَٱلۡأُولَىٰٓ ٢٥ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّمَن يَخۡشَىٰٓ ٢٦

15. Shin labarin Musa ya zo maka?

16. Lokacin da Ubangijinsa Ya kirawo shi a kwari mai tsarki, (watau) Ɗuwa?

17. (Aka ce da shi): Ka tafi zuwa ga Fir'auna, haƙiƙa shi ya yi ɗagawa.

18. Sai ka ce: "Shin zai yiwu gare ka kuwa ka tsarkaka?
19. "In kuma shiryar da kai zuwa ga Ubangijinka, sai ka ji tsoron Sa?

20. Sai ya nuna masa babbar aya.

21. Sai ya ƙaryata ya kuma kangare.

22. Sannan ya ba da baya yana ta gaggawa.

23. Sai ya tattara (jamaʾarsa) sai ya yi shela.

24. Sai ya ce, "Ni ne ubangijinku mafi girma!"

25. Saboda haka Allah Ya kama shi da azabar lahira (watau Jahannama) da ta duniya (watau nutse wa a ruwa).

26. Lalle a game da wannan tabbas akwai izina ga wanda yake tsoron (Allah).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba wa Manzonsa (ﷺ) labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) yayin da ya aike shi zuwa ga Firʾauna da jamaʾarsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, shin labarin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo masa tare da babban maƙiyinsa Firʾauna lokacin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kirawo shi ya yi magana da shi a kwarin *Ɗuwa* mai tsarki? Watau wani wuri ne kusa Dutsen Ɗuri, inda Allah ya ba shi manzanci ya kuma umarce shi da ya tunkari Firʾauna Sarkin Misra, domin kuwa ya ƙetare duk wasu iyakokin Allah, ya kuma shimfiɗa mulki na zalunci a kan Banu Israʾila. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da ya yi wa Firʾauna tayin ko zai tsarkaka cikin tausasan kalmomi na hikima, ya yi watsi da aikata kafirci da zalunci ya musulunta, shi kuma Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya shiryar da shi zuwa sanin Ubangijinsa mahaliccinsa, don ya sami tsoronsa ya aikata abin da zai jawo masa yardarsa ya guji duk abin da zai sa ya yi fushi da shi. Amma sai Firʾauna ya bijire wa tayin da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya yi masa.
Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) nan take ya nuna wa Firʾauna mafi girman ayoyinsa masu nuna lalle shi Manzon Allah ne, watau ya nuna masa hannunsa mai haske kamar fitila ba tare da wata cuta ba da kuma sandarsa mai rikiɗa ta zama macijiya. Amma Firʾauna bai yi wata-wata ba sai ya ƙaryata waɗannan ayoyin, ya bijire wa yin imani da gaskiyar da Annabi Musa ya zo masa da ita. Bai ma tsaya iya nan ba, sai da ya shiga tattara rundunoninsa don faɗa da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), ya yi shela cikin jamaʾarsa da cewa, shi ne ubangijinsu mafi girma, don haka kada su yi wa kowa biyayya sai shi kaɗai.
Sai kuwa mutanen Firʾauna suka yarda suka bi shi a kan ɓatansa, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya damƙe shi da uƙubar farko ta nan duniya ya nutsar da shi a cikin ruwa, da kuma uƙubar ƙarshe yayin da zai shigar da shi mafi tsananin azabar wuta a lahira.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a cikin irin wannan uƙuba da ya yi wa Firʾauna da mutanensa akwai izina da waʾazi ga wanda yake tsoron Allah.

****

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittar sama duk kuwa da girman da take da shi da ƙarfinta da ɗaukakarta, babban dalili ne mai nuna cikakkiyar Ƙudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ta sake raya matattu.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya shimfiɗa ƙasa ne bayan ya gama halittar sama, tare da cewa halittar ƙasa ta gabaci halittar sama, kamar yadda ya zo a cikin '*Suratul Baƙara'*, aya ta 29, da '*Suratu Fussilat'*,

aya ta tara zuwa ta 11. Ma'anar shimfiɗa ƙasa kuwa shi ne abin da ya zo a aya ta 31 da 32 a wannan Surar.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ruwa da tsirrai da ya samar a bayan ƙasa don amfanin dabbobin mutane, domin duk abin da ya amfani dabbobinsu to su ya amfanar, domin dabbobinsu suna daga cikin kayan amfaninsu. Sai dai ambaton dabbobi a nan domin a yi nuni ne ga cewa, su ma suna tarayya da ɗan'adam wajen amfanuwa da albarkatun ƙasa, to amma shi ɗan'adam ya kamata ya ɗara su a nan, watau ya ɗauki izina da wa'azi daga ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa a bayan ƙasa, kamar yadda ya zo a *'Suratu Ɗaha'*, aya ta 54.

Suratun Nazi'at (27-33)

ءَأَنتُمۡ أَشَدُّ خَلۡقًا أَمِ ٱلسَّمَآءُۚ بَنَىٰهَا ٢٧ رَفَعَ سَمۡكَهَا فَسَوَّىٰهَا ٢٨ وَأَغۡطَشَ لَيۡلَهَا وَأَخۡرَجَ ضُحَىٰهَا ٢٩ وَٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ دَحَىٰهَآ ٣٠ أَخۡرَجَ مِنۡهَا مَآءَهَا وَمَرۡعَىٰهَا ٣١ وَٱلۡجِبَالَ أَرۡسَىٰهَا ٣٢ مَتَٰعًا لَّكُمۡ وَلِأَنۡعَٰمِكُمۡ ٣٣

27. Yanzu ku ne halittarku ta fi tsanani ko kuwa sama wadda Shi ne Ya gina ta?

28. Ya ɗaukaka rufinta Ya kuma daidaita ta.

29. Ya lulluɓe darenta da duhu Ya kuma fitar da hasken hantsinta.

30. Ƙasa kuma bayan haka Ya shimfiɗa ta.

31. Ya fitar da ruwanta da makiyayarta daga gare ta.

32. Duwatsu kuma Ya kafa su.

33. Don jin daɗinku da na dabbobinku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kafa wa mushirikai masu ƙaryata tashin alƙiyama wata ƙaƙƙarfar hujja ta hankali, inda ya tambaye su cewa, wai shin halittarsu ce ta fi ba da wahala ko kuma halittar sama wadda Allah ne ya gina ta da cikar Ƙudurarsa? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ɗaukaka rufinta sama sannan ya daidaita ta babu wata ɓaraka ko tsagewa ko wani aibi a tare da ita. Sannan kuma idan rana ta faɗi sai ya sanya darenta ya yi duhu ko'ina a bayan ƙasa, kuma idan rana ta hudo da hantsi sai ko'ina ya yi haske. Kuma bayan ya gama halittar sama sai ya dawo ya shimfiɗa ƙasa ya sanya mata ababan amfaninta waɗanda suka haɗa da ruwa da ya fitar da idanuwansu masu kwarara a bayan ƙasa, ya fitar da tsirrai waɗanda dabbobi suke ci a wuraren kiwonsu. Duwatsu kuwa ya kafa su a cikinta, don kada ta riƙa tangal-tangal da na bayanta.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa mutane cewa, duk waɗannan ababan amfani ne gare su da dabbobinsu. Don haka wanda ya ƙagi irin waɗannan halittu, ai sake dawo musu da ransu bayan sun mutu ba abu ne da zai gagare shi ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin tsoron ranar tashin alƙiyama wanda ya kere kowane abin ban tsoro.

2. Abubuwan ban tsoro na ranar alƙiyama za su tunatar da mutum ayyukansa da ya yi a duniya, a lokacin zai yi burin daɗuwar kyawawan ayyukansa ko da daidai da ƙwayar komayya ne, zai kuma yi baƙin cikin ƙaruwar munanan ayyukansa ko da daidai da ƙwayar komayya ne.

3. Ɗagawa da ƙetare iyakokin Allah da fifita rayuwar duniya a kan ta lahira suna daga cikin dalilai masu sabbaba shiga wutar Jahannama.

4. Tsoron tsayuwa a gaban Allah ranar alƙiyama da nisantar bin son zuciya, sababi ne na shiga Aljanna.

Suratun Nazi'at (34-41)

مَتَٰعًا لَّكُمۡ وَ لِأَنۡعَٰمِكُمۡ ﴿٣٣﴾ فَإِذَا جَآءَتِ ٱلطَّآمَّةُ ٱلۡكُبۡرَىٰ ﴿٣٤﴾ يَوۡمَ يَتَذَكَّرُ ٱلۡإِنسَٰنُ مَا سَعَىٰ ﴿٣٥﴾ وَبُرِّزَتِ ٱلۡجَحِيمُ لِمَن يَرَىٰ ﴿٣٦﴾ فَأَمَّا مَن طَغَىٰ ﴿٣٧﴾
وَءَاثَرَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ﴿٣٨﴾ فَإِنَّ ٱلۡجَحِيمَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ﴿٣٩﴾ وَأَمَّا مَنۡ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ وَنَهَى ٱلنَّفۡسَ عَنِ ٱلۡهَوَىٰ ﴿٤٠﴾ فَإِنَّ ٱلۡجَنَّةَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ﴿٤١﴾

34. Sannan idan mafi girman busar ƙaho ta zo (watau busa ta biyu).

35. A ranar da mutum zai tuna abin da ya aikata.

36. Aka kuma bayyana (wutar) Jahimu ga kowane mai gani.

37. To (a wannan ranar) duk wanda ya yi ɗagawa.

38. Ya kuma fifita rayuwar duniya.

39. To lalle (wutar) Jahimu ita ce makoma.

40. Duk wanda kuma ya ji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa, ya kuma hana zuciya bin abin da take so.

41. To lalle Aljanna ita ce makoma.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi mushirikai masu ƙaryata tashin alƙiyama da su kiyayi ranar da za su yi nadama kuma nadamarsu ba za ta yi musu amfanin komai ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana musu cewa, idan har busar ƙaho ta biyu ta zo wadda tsoron da ke cikinta zai mamaye komai, to alƙiyama ta tsaya ke nan, kuma a ranar ne mutum zai tuna duk abin da ya aikata a duniya mai kyau da mummuna, a kuma bayyanar da wutar Jahannama a sarari don kowa ya gan ta tana jiran ta karɓi 'ya'yanta. A nan ne mutane za su kasu kashi biyu: Duk wanda ya ƙetare iyakokin Allah da kafirci da saɓo, ya kuma fifita rayuwar duniya mai ƙarewa a kan rayuwar lahira mai wanzuwa, to wannan wutar Jahannama ce makomarsa. Amma kuma wanda ya ji tsoron tsayuwa a gaban Ubangijinsa, ya hana ransa bin son zuciyarsa, to wannan Aljanna ce makomarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babu wanda ya san lokacin zuwan ranar alƙiyama sai Allah shi kaɗai.

2. Mai amfana da gargadìn Annabi (ﷺ) game da ranar alƙiyama shi ne wanda yake jin tsoron tsayuwa a gaban Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) don yi masa hisabi. Amma wanda bai yi imani da ranar lahira ba, to wannan ba zai amfana da duk wani gargadì da tsoratarwa da ake yi masa ba.

3. Rayuwar duniya ba a bakin komai take ba idan an kwatantata da ta lahira.

Suratun Nazi'at (42-46)
يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلسَّاعَةِ أَيَّانَ مُرْسَىٰهَا ﴿٤٢﴾ فِيمَ أَنتَ مِن ذِكْرَىٰهَآ ﴿٤٣﴾ إِلَىٰ رَبِّكَ مُنتَهَىٰهَآ ﴿٤٤﴾ إِنَّمَآ أَنتَ مُنذِرُ مَن يَخْشَىٰهَا ﴿٤٥﴾ كَأَنَّهُمْ يَوْمَ يَرَوْنَهَا لَمْ يَلْبَثُوٓاْ إِلَّا عَشِيَّةً أَوْ ضُحَىٰهَا ﴿٤٦﴾

42. Suna tambayar ka game da alƙiyama, yaushe ne lokacinta?

43. Me ya gama ka da ambaton lokacinta?

44. Zuwa ga Ubangijinka ne iyakacin saninta yake.

45. Kai dai kawai mai gargadìn wanda yake tsoron ta ne.

46. Kai ka ce su ranar da za su gan ta ba su zauna ba (a duniya) face wani yammaci ko kuma hantsinta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda mushirikai masu ƙaryata zuwan ranar alƙiyama suka matsa wa Manzon Allah (ﷺ) da tambayar ƙwaƙwa game da takamaiman lokacin zuwanta da nufin su ƙure shi, ba wai don su gamsu su yi imani ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, babu abin da ya haɗa Manzonsa (ﷺ) da sanin takamaiman lokacin alƙiyama, domin ba wannan ne aikin da aka ɗora masa ba; ilimin sanin haka yana ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai bai kuma sanar da kowa shi ba. Shi Manzon Allah (ﷺ) aikinsa shi ne kawai ya gargadì duk wanda yake tsoron ranar tashin alƙiyama domin shi ne zai amfana da gargadìnsa. Su kuwa mushirikai masu ƙaryata ta duk ranar da za su gan ta, za su ga kamar ma ba su rayu a duniya ba sai gwargwadon yini ɗaya kacal ko hantsin yini guda, watau farkonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da cewa Annabi (ﷺ) mutum ne kamar sauran mutane, abin da yake bijiro musu na farin ciki ko baƙin ciki da nuna damuwa yana bijiro masa shi ma.

2. An bayyana lalurar Abdullahi ɗan Ummu Maktum (Allah ya kara masa yarda) ta makanta, don nuna uzurinsa na fuskanto Manzon Allah (ﷺ) da tambaya alhalin yana cikin wani zarafi, saboda rashin gani da yake fama da shi.

3. Sanin abin da yake cikin zukata aikin Allah ne shi kaɗai, don haka Manzon Allah (ﷺ) bai san wane ne zai tsarkaka ba wane ne kuma ba zai tsarkaka ba. Wannan shi ma uzuri ne ga Manzon Allah (ﷺ) game da mayar da hankali da ya yi ga shugabannin Ƙuraishawa ya ƙyale Ɗan Ummu Maktum (Allah ya kara masa yarda) don yana zaton za su musulunta.

4. Wadata da ni'ima ta duniya takan hana wasu amfana da wa'azi da faɗakarwa.

5. Abin da ya dace ya kuma fi zama wajibi ga mai waʾazi shi ne ya fi mayar da hankalinsa ga wanda ya kawo kansa gare shi yana mai nuna buƙatarsa, ba wanda wadatarsa ta hana shi ya nemi sani ko ya nuna buƙatarsa ga wani alheri ba. Rashin tsarkakarsa da amfanuwarsa da waʾazin mai waʾazi ba za ta cutar da mai waʾazin da komai ba, domin wannan ba a hannunsa yake ba. Don haka ba a barin maslaha ta dahir a kama wadda ba ta wuce zato ba.

6. Tabbatar da cewa, Alƙurʾani daga Allah ne ba maganar Manzon Allah ba ce, domin mutum ba ya fitowa ya zargi kansa da kansa irin haka.

7. Falalar Abdullahi ɗan Ummu Maktum da kyakkyawar shaidar tsarkaka da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa.



80-Suratu Abasa

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da *'Suratu Abasa'*, watau da kalmar farko da ta zo a cikinta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya,* babu wani saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ashirin da huɗu (24) a jerin saukar surorin Alƙurʾani, ta sauka bayan *'Suratun Najmi'* kafin '*Suratul Kadri*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta arbaʾin da biyu ne (42) a wurin malaman Makka da Madina da Kufa. Amma a wurin malaman Basra arbaʾin da ɗaya ne (41), a wurin malaman Sham kuwa ayoyinta arbaʾin ne (40) daidai.

5. Dalilin Saukarta:
Wata rana Manzon Allah (ﷺ) yana zaune tare da wasu manyan Kuraishawa, irin su Abu Jahl da Utbatu ɗan Rabiʾatu, yana ƙoƙarin shawo kansu su musulunta, yana kuma ganin alamar haɗin kai daga gare su, sai ga Abdullahi ɗan Ummu Maktum (Allah ya ƙara masa yarda) wani makaho da ya musulunta, ya zo yana yi wa Manzon Allah (ﷺ) wata magana, sai Manzon Allah (ﷺ) ya kawar da kansa daga gare shi ya murtuke masa fuska, domin gudun kada ya shagaltar da shi daga waɗannan manyan Kuraishawan da yake tsammanin za su musulunta; shi kuma yana ganin musuluntarsu ba ƙaramin cin nasara ba ce ga daʾawarsa a lokacin. Sai Allah ya saukar masa da wannan Surar yana zargin sa a kan haka. Tun daga lokacin Annabi (ﷺ) ya ci gaba da girmama Abdullahi ɗan Ummu Maktum da jawo shi a jiki. [Dubi, *Mausuʾatut Tafsiril Maʾasur*, juzuʾi na 22, shafi na 696-699].

6. Babban Jigonta:
Haƙiƙanin manufar karantarwar Alƙur'ani da girman darajar wanda yake amfanuwa da shi da ƙaskancin wanda yake bijire masa.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin abin da ya faru tsakanin Manzon Allah (ﷺ) da Abdullahi ɗan Ummu Maktum (Allah ya ƙara masa yarda) da nuna wa Manzon Allah (ﷺ) haƙiƙanin halayen mushirikai da halin Abdullahi ɗan Ummu Maktum (Allah ya kara masa yarda).
• Haƙiƙanin koyarwar Alƙur'ani da amfaninsa ga mai son ya amfana da shi.
• Tabbatar da tashi bayan mutuwa wanda mushirikai suke ƙaryatawa.
• Tuna wa masu ƙaryata gaskiya ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu don su gode masa.
• Matsayin muminai raunana a wurin Allah da girman darajarsu da ƙaskancin kafirai a wurinsa da wulaƙancinsu.

Suratu Abasa (1-10)
عَبَسَ وَتَوَلَّىٰٓ ۝١ أَن جَآءَهُ ٱلۡأَعۡمَىٰ ۝٢ وَمَا يُدۡرِيكَ لَعَلَّهُۥ يَزَّكَّىٰٓ ۝٣ أَوۡ يَذَّكَّرُ فَتَنفَعَهُ ٱلذِّكۡرَىٰٓ ۝٤ أَمَّا مَنِ ٱسۡتَغۡنَىٰ ۝٥ فَأَنتَ لَهُۥ تَصَدَّىٰ ۝٦ وَمَا عَلَيۡكَ أَلَّا يَزَّكَّىٰ ۝٧ وَأَمَّا مَن جَآءَكَ يَسۡعَىٰ ۝٨ وَهُوَ يَخۡشَىٰ ۝٩ فَأَنتَ عَنۡهُ تَلَهَّىٰ ۝١٠

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ya ɗaure fuska, ya kuma ba da baya.

2. Don makaho ya zo masa.

3. Me kuma zai sanar da kai cewa watakila shi ne zai tsarkaka?

4. Ko ya waʾazantu, sai waʾazin ya amfane shi?

5. Amma wanda ya wadatu (daga waʾazinka).

6. To kai shi kake fuskanta.

7. Babu kuwa komai a kanka don ya ƙi ya tsarkaka

8. Amma kuma wanda ya zo maka yana sauri.

9. Alhali kuma shi yana tsoron (Allah).

10. To kai shi kake kawar wa da kai.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da labarin Annabi (ﷺ) tare da Abdullahi ɗan Ummu Maktum wanda ya kasance makaho ne kuma ɗaya daga cikin waɗanda suka shiga Musulunci tun a Makka, suka kuma yi hijira zuwa Madina. Ya zo wurin Manzon Allah (ﷺ) yana yi masa tambaya don ya ƙaru da sanin hukunce-hukuncen addininsa, shi kuma Annabi (ﷺ) hankalinsa yana kan shuwagabannin Ƙuraishawa waɗanda yake ƙoƙarin janyo hankulansu zuwa ga Musulunci. Da Ibnu Ummi Maktum (Allah ya ƙara masa

yarda) ya matsa wa Annabi (ﷺ) da tambaya sai shi kuma ya ɓata fuskarsa ya kawar da kansa daga gare shi, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan Surar yana zargin sa (ﷺ) cewa, ya murtuke fuskarsa ya juya baya domin makaho Abdullahi ɗan Ummu Maktum (Allah ya ƙara masa yarda) ya zo yana tambayar sa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, me ya ya sanar da shi cewa, walaʾalla wannan makahon da ya haɗe wa fuska ya juya masa baya zai tsarkaka daga zunubansa a dalilin waʾazinsa da karantarwarsa, ko ya amfana da abin da zai ji na waʾazi nan gaba?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, amma wanda Manzon Allah (ﷺ) yake ganin ya wadatu da dukiyarsa ba ya buƙatar wani waʾazi, me zai sa ya fuskance shi har ya rajaʾa a kansa? Kuma me zai sami Manzo (ﷺ) idan wannan mutum ya ƙi tsarkaka daga laifukansa ya ƙi ya tuba zuwa ga Allah? Watau babu wata cutuwa da za ta same shi don waɗannan manyan kafiran sun ƙi karɓar Musulunci.
To amma dangane da shi Abdullahi ɗan Ummi Maktum (Allah ya ƙara masa yarda) da ya zo masa yana gaggawa yana son ya ƙaru da wani alheri, kuma yana tsoron Ubangiji, me zai sa shi Manzo (ﷺ) zai shagala da wasu mushirikai ya ƙyale shi?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babbar manufar Alƙurʾani ita ce waʾazantarwa da tunatarwa.

2. Tabbatar wa ɗanʾadam iko na ya karɓi gaskiya idan ya ga dama ko ya bijire, don a yi masa sakayya gwargwadon aikinsa mai kyau ko mummuna.

3. Girman matsayin Alƙurʾani da darajarsa a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Kariyar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa littafinsa Alƙurʾani daga duk wata gurɓatawa ko jirkitawa.

Suratu Abasa (11-16)

كَلَّآ إِنَّهَا تَذۡكِرَةٞ ١١ فَمَن شَآءَ ذَكَرَهُۥ ١٢ فِي صُحُفٖ مُّكَرَّمَةٖ ١٣ مَّرۡفُوعَةٖ مُّطَهَّرَةِۭ ١٤ بِأَيۡدِي سَفَرَةٖ ١٥ كِرَامِۭ بَرَرَةٖ ١٦

11. Abin ba haka yake ba, lalle (wannan da'awar) waʾazi ne.

12. Don haka wanda ya ga dama ya waʾazantu.

13. (Wannan Alƙur'ani) yana cikin takardu ababan girmamawa.

14. Maɗaukaka, tsarkaka.

15. A hannayen jakadu (malaʾiku).

16. Manya masu biyayya.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waʾazin da ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya yi wa bayinsa tunatarwa ce kawai ba wani abu ne daban ba, don haka wanda ya so sai ya waʾazantu da wannan tunatarwar ya yi aiki da abin da Alƙurʾani ya zo masa da shi, domin Alƙurʾani littafi ne mai girman daraja, wanda yake cikin takardu masu daraja a wurin wasu malaʾiku maɗaukaka a kuma wani wuri maɗaukaki, abin tsarkakewa, duk wata najasa ba za ta taɓa su ba, kuma wannan Alƙura'ani yana

hannun wasu mala'iku jakadun Allah masu girma a wurin Ubangijinsu, masu yawan aikata alheri da biyayya ga Allah.

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda duk ya zamanto gwani ne wajen karatun Alƙur'ani to yana tare da mala'iku jakadu masu girma, masu biyayya. Wanda kuwa yake shan wahala wajen karatun Alƙur'ani, to yana da lada biyu." [Bukhari #4937 da Muslim #798].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin butulcin kafiri game da ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa tun yana cikin mahaifiyarsa har ya zo duniya ya gama rayuwarsa, don haka ne ya cancanci la'anar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Cikar Ƙudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wajen halittar mutum daga ɗigon maniyyi da ajiye shi a cikin mahaifa mataki-mataki har lokacin cikar halittarsa.

3. Fitowar jariri daga cikin mahaifiyarsa wata babbar ni'ima ce ga ɗan'adam kuma aya ce daga cikin ayoyin Ƙudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

4. Binne mamaci a cikin ƙabarinsa wata ni'ima ce babba kuma alama ce ta darajta gawar ɗan'adam da karrama shi.

Suratu Abasa (17-23)
قُتِلَ ٱلۡإِنسَٰنُ مَآ أَكۡفَرَهُۥ ١٧ مِنۡ أَيِّ شَيۡءٍ خَلَقَهُۥ ١٨ مِن نُّطۡفَةٍ خَلَقَهُۥ فَقَدَّرَهُۥ ١٩ ثُمَّ ٱلسَّبِيلَ يَسَّرَهُۥ ٢٠ ثُمَّ أَمَاتَهُۥ فَأَقۡبَرَهُۥ ٢١ ثُمَّ إِذَا شَآءَ أَنشَرَهُۥ ٢٢ كَلَّا لَمَّا يَقۡضِ مَآ أَمَرَهُۥ ٢٣

17. An la'anci mutum, me ya kai tsananin kafircinsa!

18. Shin daga wane abu ne (Allah) Ya halicce shi?

19. Daga maniyyi ne Ya halicce shi, sannan Ya ƙaddara shi (matakai a halitta).

20. Sannan tafarki (na rayuwa) Ya hore masa shi.

21. Sannan Ya kashe shi, sai Ya sa shi cikin ƙabarinsa.

22. Sannan in Ya ga dama Ya tashe shi.

23. Fafau (zaton mutum) ba haka ne ba, har yanzu bai aikata abin da (Allah) Ya umarce shi ba.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗi ɗan'adam wanda dukiyarsa da ruɗin duniya suka ruɗe shi suka sanya shi girman kai, har ya butulce wa Allah mahaliccinsa. Allah (Mai tsarki da

ɗaukaka) ya laʾanci kafiri, wanda saboda tsananin kafircinsa ga Allah ya zama wani abin mamaki, domin ya manta da wane abu ne Allah ya halicce shi har yake yi masa girman kai a bayan ƙasa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da shi cewa, ya halicce shi ne fa daga wani wulaƙantaccen ruwa, watau ɗigon maniyyi wanda aka sanya shi a cikin mahaifiyarsa Allah kuma ya ƙaddara halittarsa mataki-mataki har ya gama cika masa halittarsa, sannan ya hore masa hanyar fitowa daga cikin mahaifiyarsa zuwa duniya, ya ƙayyade masa iya rayuwar da zai yi a duniya, da zarar ajalinsa ya zo kuma ya karɓi ransa, ya sanya shi a ƙabarinsa wanda zai yi ta zama a cikinsa har zuwa lokacin tashinsa, domin yi masa hisabi da sakamako a bisa yadda Allah mahaliccinsa ya ga dama.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da kafiri cewa, alʾamarin ba kamar yadda yake zato ne ba na ganin kamar ya sauke haƙƙoƙin Allah da suke kansa, ko kusa, sam bai aikata abin da Allah ya wajabta masa ba na farillai. Har yanzu nauyi yana nan a kansa, sai kuma an tambaye shi a kai ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jan hankalin ɗanʾadam zuwa ga yin tunani game da abin da yake kusa da shi na buƙatarsa ta yau da kullum, watau abincinsa, domin ya ga girman Ƙudurar Allah wajen samar masa da shi. Don haka ƙaryata tashi bayan mutuwa daidai yake da ƙaryata Ƙudurar Allah a kan samar da abincin ɗanʾadam.

2. Yawan niʾimomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗanʾadam a sama da ƙasa don ya zamanto mai godiya a gare shi da bauta masa shi kaɗai ba tare da haɗa shi da abokin tarayya ba.

Suratu Abasa (24-32)
فَلۡيَنظُرِ ٱلۡإِنسَٰنُ إِلَىٰ طَعَامِهِۦٓ ٢٤ أَنَّا صَبَبۡنَا ٱلۡمَآءَ صَبّٗا ٢٥ ثُمَّ شَقَقۡنَا ٱلۡأَرۡضَ شَقّٗا ٢٦ فَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا حَبّٗا ٢٧ وَعِنَبٗا وَقَضۡبٗا ٢٨ وَزَيۡتُونٗا وَنَخۡلٗا ٢٩
وَحَدَآئِقَ غُلۡبٗا ٣٠ وَفَٰكِهَةٗ وَأَبّٗا ٣١ مَّتَٰعٗا لَّكُمۡ وَلِأَنۡعَٰمِكُمۡ ٣٢

24. To mutum ya yi duba zuwa ga abincinsa mana?

25. Cewa lalle Mu Muka zubo da ruwan sama zubowa.

26. Sannan Muka tsaga ƙasa tsagawa.

27. Sai Muka tsiro da ƙwaya daga cikinta.

28. Da inabai da ciyayi.

29. Da zaitun da dabino.

30. Da gonaki cike da itatuwa.

31. Da kayan marmari da makiyaya.

32. Don jin daɗinku da na dabbobinku.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin ɗanʾadam ne a kan ya duba niʾimomin da ya yi masa waɗanda suke nuna cikar Ƙudurarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mutum da ya dubi abincinsa da yake ci, ƙaƙa ya samu? Ya tabbatar masa cewa,

asalinsa daga ruwan sama ne mai zuba da yawa da ƙarfi, sannan Allah ya tsaga ƙasa ya fito da tsirran cikinta, waɗanda suka haɗa da masu ƙwaya kamar alkama da masara da danginsu, ya kuma fitar da inabi da abincin dabbobi da zaitun da dabino, ya fitar da gonaki masu cike da bishiyoyi iri-iri da kayan marmari da abin da dabbobinsu za su ci yayin kiwonsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu duk waɗannan ni'imomi ne domin jin daɗinsu da na dabbobinsu waɗanda su ma ya halicce su ne ya hore musu su don amfaninsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da busa ta biyu a cikin ƙaho da tsananin ƙararta.

2. Duk wata dangantaka ta kusa ko ta nesa ba za ta amfani mutum ba a ranar alƙiyama sai aikinsa kaɗai.

3. Saboda tsananin tsoron ranar alƙiyama kowa ta kansa yake, har annabawa za su riƙa cewa ne, *'nafsi nafsi'*, watau ta-kaina ta-kaina.

4. Mutane za su kasu kashi biyu a ranar alƙiyama; 'yan Aljanna masu cike da farin ciki; da 'yan wuta masu cike da baƙin ciki.

Suratu Abasa (33-42)
فَإِذَا جَآءَتِ ٱلصَّآخَّةُ ﴿٣٣﴾ يَوۡمَ يَفِرُّ ٱلۡمَرۡءُ مِنۡ أَخِيهِ ﴿٣٤﴾ وَأُمِّهِۦ وَأَبِيهِ ﴿٣٥﴾ وَصَٰحِبَتِهِۦ وَبَنِيهِ ﴿٣٦﴾ لِكُلِّ ٱمۡرِيٕ مِّنۡهُمۡ يَوۡمَئِذٖ شَأۡنٞ يُغۡنِيهِ ﴿٣٧﴾ وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٖ مُّسۡفِرَةٞ ﴿٣٨﴾ ضَاحِكَةٞ مُّسۡتَبۡشِرَةٞ ﴿٣٩﴾ وَوُجُوهٞ يَوۡمَئِذٍ عَلَيۡهَا غَبَرَةٞ ﴿٤٠﴾ تَرۡهَقُهَا قَتَرَةٌ ﴿٤١﴾ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَفَرَةُ ٱلۡفَجَرَةُ ﴿٤٢﴾

33. Sannan idan mai sa kurunta ta zo (watau busa ta farko).

34. A ranar da mutum yake guje wa ɗan'uwansa.

35. Da uwarsa da ubansa.

36. Da matarsa da 'ya'yansa.

37. Kowane mutum daga cikinsu a wannan ranar yana da lamarin da ya sha kansa.

38. Wasu fuskoki a wannan ranar masu haske ne.

39. Masu dariya, masu farin ciki.

40. Wasu fuskokin kuma a ranar akwai ƙura a kansu.

41. Baƙin ciki zai lulluɓe su.

42. Waɗannan su ne kafirai maɓarnata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tabbatar da cewa, ba makawa sai an tashi aƙliyama, don haka idan aka yi busa ta biyu mai tsananin ƙarfi da za ta kurumtar da kunnuwa saboda tsananin ƙararta, to a wannan ranar ne mutum zai guje wa ɗan'uwansa da mahaifinsa da mahaifiyarsa

da matarsa da ‘ya’yansa, domin kowa a wannan ranar al’amarinsa ya ishe shi, saboda tsananin tsoro da firgici.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: “Za a tattara ku (ranar alƙiyama) babu takalmi, tsirara, masu loɓa.” Sai wata daga cikin matansa ta ce: “Shin muna kallon al’aurar junanmu?” Sai ya ce: “Ya wance, (*Kowane mutum daga cikinsu a wannan ranar yana da lamarin da ya ishe shi*.)” [Tirmizi #3622].

An karɓo daga Saudatu ‘yar Zam’ah (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Za a tashi mutane marasa takalma, tsirara masu loɓa, gumi zai zo musu iya wuya, ya kai har fatun kunnuwansu.” Sai ta ce: Sai na ce: Ya Manzon Allah, na shiga uku! Za mu riƙa kallon junanmu? Sai ya ce: “Mutane ba ta wannan suke yi ba.” Sai ya karanta faɗar Allah: “*Kowane mutum daga cikinsu a wannan ranar yana da lamarin da ya ishe shi*.” [Alhakim #3898].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mutane a ranar za su kasu kashi biyu:

Kashi na farko, ‘yan Aljanna waɗanda fuskokinsu za su yi ta haske suna masu dariya, cike da farin ciki saboda ganin tanadin rahama da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu.
Na biyu, su ne ‘yan wuta waɗanda fuskokinsu za su yi ɓutu-ɓutu da ƙura, duhu ya lulluɓe su ta ko’ina, sun ɗebe ƙaunar samun rahamar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗannan su ne suka haɗa siffar kafirci da fajirci, watau suka kafirce wa Allah da ni’imominsa, suka kuma keta iyakokinsa da ayyukan saɓonsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da aukuwar ranar alƙiyama.

2. Rushewar duk wani tsari da duniya take gudana a kansa, wanda ya danganci rana da wata da taurari da duwatsu da koguna.

3. Waɗannan siffofin da Allah ya siffanta ranar alƙiyama da su, siffofi ne da za su jefa tsoro da fargaba a cikin zukata, su sanya musu tsoron wannan rana, don su tashi domin yi mata kyakkyawan tanadi da guje wa aikata abin da zai jawo musu taɓewa da hasara a cikinta.

4. Girman laifin kashe yara mata da rai da hisabin da Allah zai yi tsakanin yaran da aka kashe da waɗanda suka kashe su.

81-Suratut Takwir

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
An fi sanin ta da '*Suratut Takwir'*. A littafin *Sahihul Bukhari* da *Jami'ut Tirmizi* sun kira ta da '*Suratu Izas Shamsu Kuwwirat'*. Ta samu sunanta ne da kalmar '*Kuwwirat*' da ta zo a ayarta ta farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* ba tare da wani saɓani ba.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta bakwai (7) a jerin saukar surorin Alƙur'ani. Ta sauka bayan *'Suratul Fatiha' kafin* '*Suratul A'ala'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin da tara ne (29) daidai.

5. Falalarta:
An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wanda zai yi farin cikin ya ga kamar yana ganin alƙiyama ƙuru-ƙuru da idanunsa, to ya karanta *'Izas Shamsu Kuwwirat'* da '*Izas Sama'un Shaƙkat'* da '*Suratu Hudu'*." [Ahmad #4806 da Tirmizi #3333].

6. Babban Jigonta:
Tana magana a kan alamomin tashin alƙiyama yayin da tsarin duniya zai ruguje.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Wasu muhimman alamomi na tabbatar da zuwan alƙiyama.
• Tabbatar da sakamakon ayyuka a ranar alƙiyama.

• Girman Alƙur’ani wanda ya zo da bayanin tashi bayan mutuwa da mushirikai suke ƙaryatawa.

Suratut Takwir (1-14)

إِذَا ٱلشَّمۡسُ كُوِّرَتۡ ١ وَإِذَا ٱلنُّجُومُ ٱنكَدَرَتۡ ٢ وَإِذَا ٱلۡجِبَالُ سُيِّرَتۡ ٣ وَإِذَا ٱلۡعِشَارُ عُطِّلَتۡ ٤ وَإِذَا ٱلۡوُحُوشُ حُشِرَتۡ ٥ وَإِذَا ٱلۡبِحَارُ سُجِّرَتۡ ٦ وَإِذَا ٱلنُّفُوسُ زُوِّجَتۡ ٧ وَإِذَا ٱلۡمَوۡءُۥدَةُ سُئِلَتۡ ٨ بِأَيِّ ذَنۢبٖ قُتِلَتۡ ٩ وَإِذَا ٱلصُّحُفُ نُشِرَتۡ ١٠ وَإِذَا ٱلسَّمَآءُ كُشِطَتۡ ١١ وَإِذَا ٱلۡجَحِيمُ سُعِّرَتۡ ١٢ وَإِذَا ٱلۡجَنَّةُ أُزۡلِفَتۡ ١٣ عَلِمَتۡ نَفۡسٞ مَّآ أَحۡضَرَتۡ ١٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Idan rana aka naɗe ta.

2. Idan kuma taurari suka farfaɗo.

3. Idan kuma duwatsu aka tafiyar da su.

4. Idan kuma raƙuma masu ciki aka bar su ba makiyayi.

5. Idan kuma namun daji aka tattara su.

6. Idan kuma koguna aka rura su (suka zama wuta).

7. Idan kuma rayuka aka haɗa su (da jinsinsu).

8. Idan kuma yarinyar da aka binne da rai aka tambaye ta.

9. Da wane laifi ne aka kashe ta?

10. Idan kuma takardun (ayyuka) aka baza su.

11. Idan kuma sama aka ɗaye ta.

12. Idan kuma wutar Jahimu aka hura ta.

13. Idan kuma Aljanna aka kusanto da ita.

14. To kowane rai ya san abin da ya halarto (da shi na ayyuka).

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da bayanin wasu manyan abubuwan ban tsoro shida da za su faru gabanin tashin alƙiyama, da kuma wasu shida da za su auku bayan tashinta.
Na farko, shi ne lokacin da za a tattara rana da wata wuri guda a tafiyar da haskensu.
An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Rana da wata za a naɗe kowannensu a ranar alƙiyama.” [Bukhari #3200].
Na biyu, su kuma taurari idan suka warwatse haskensu ya bice.
Na uku, idan su kuma duwatsu aka matsar da su daga wurarensu, watau aka dandaƙe su suka zama kamar rairayi ko ƙura abar ɗaiɗaitawa.

Na huɗu, idan raƙuma masu ciki aka watsar da su babu mai kula da su duk da irin darajarsu a idon makiyaya.
Na biyar, idan namun daji aka tattara su wuri guda tare da 'yan'adam.
Na shida, idan koguna aka rura su suka zama wuta.
Sannan ya ambaci abubuwa shida waɗanda za su biyo bayan tashin alƙiyama.
Na farko, idan aka haɗa rayuka da jinsinsu, watau aka haɗa fajirai wuri guda, mutanen kirki wuri guda.
Na biyu, idan yarinyar da aka binne ta da rai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye ta, da wane laifi ne mai kisan ta ya kashe ta ? Su ne yara mata da iyayensu suka riƙa binne su da rai a zamanin jahiliyya kafin zuwan Musulunci, wai don tsoron talauci ko gudun su jawo musu abin kunya.
Na uku, idan aka baza takardun ayyukan bayi don kowa ya karanta takardarsa da kansa.
Na huɗu, idan aka ɗaye sama kamar yadda ake feɗe fata daga jikin dabba.
Na biyar, idan aka rura wutar Jahima ruruwar da ba ta taɓa yin irinta ba.
Na shida, idan aka matso da Aljanna dab da masu taƙawa.
To idan waɗannan abubuwan guda goma sha biyu suka faru, a lokacin kowane rai zai san ayyukan da ya gabatar a baya domin wannan ranar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittunsa. Amma bai halatta ga wani Musulmi ya yi rantsuwa ba da Allah ba.

2. Matsayin Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) matsayi ne babba, don haka ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya keɓance shi da ɗaukar saƙo mafi girman ni'imar Allah zuwa bayinsa, watau wahayi.

3. Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) shi ne shugaban mala'iku wanda dukkansu suke yi masa biyayya.

4. Annabi (ﷺ) ya ga Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a siffarsa da Allah ya halicce shi da ita yana da fukafukai ɗari shida.

5. Annabi (ﷺ) bai ɓoye komai na wahayin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yiwo masa ba, bai bar duniya ba sai da ya gama isar da dukkan saƙwannin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba daɗi ba ragi.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bai wa ɗan'adam damar zaɓin hanyar da zai bi, mai kyau ko mummuna, amma damar ɗan'adam tana ƙarƙashin ikon Allah ne da ganin damarsa, babu abin da zai wakana sai da ganin damar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratut Takwir (15-29)
فَلَآ أُقۡسِمُ بِٱلۡخُنَّسِ ١٥ ٱلۡجَوَارِ ٱلۡكُنَّسِ ١٦ وَٱلَّيۡلِ إِذَا عَسۡعَسَ ١٧ وَٱلصُّبۡحِ إِذَا تَنَفَّسَ ١٨ إِنَّهُۥ لَقَوۡلُ رَسُولٖ كَرِيمٖ ١٩ ذِي قُوَّةٍ عِندَ ذِي ٱلۡعَرۡشِ
مَكِينٖ ٢٠ مُّطَاعٖ ثَمَّ أَمِينٖ ٢١ وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجۡنُونٖ ٢٢ وَلَقَدۡ رَءَاهُ بِٱلۡأُفُقِ ٱلۡمُبِينِ ٢٣ وَمَا هُوَ عَلَى ٱلۡغَيۡبِ بِضَنِينٖ ٢٤ وَمَا هُوَ بِقَوۡلِ شَيۡطَٰنٖ
رَّجِيمٖ ٢٥ فَأَيۡنَ تَذۡهَبُونَ ٢٦ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ لِّلۡعَٰلَمِينَ ٢٧ لِمَن شَآءَ مِنكُمۡ أَن يَسۡتَقِيمَ ٢٨ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢٩

15. To ina rantsuwa da taurari masu ɓuya.

16. Masu gudu zuwa masaukansu.

17. Da kuma dare idan ya yi duhu.

18. Da kuma asuba idan ta keto.

19. Lalle shi (Alƙur'ani) magana ce ta Manzo mai karamci.

20. Ma'abocin ƙarfi a wurin Mai Al'arshi, kuma mai babban matsayi.

21. Wanda ake yi wa biyayya ne a can (sama), amintacce.

22. Mutumin naku kuma (watau Ma'aiki) ba mahaukaci ba ne.

23. Haƙiƙa kuma ya gan shi a sararin sama mabayyani.

24. Shi kuma ba mai rowa ba ne game da wahayi.

25. Kuma shi (Alƙur'ani) ba zancen Shaiɗan ne la'ananne ba.

26. To ina za ku dosa ne?

27. Shi ba wani abu ba ne sai wa'azi ga talikai.

28. Ga wanda ya ga dama daga cikinku ya bi hanya madaidaiciya.

29. Ku kuma ba za ku iya ganin dama ba sai Allah Ubangijin talikai Ya ga dama.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, Alƙur'ani maganarsa ce wadda ya yiwo wahayinta ga Annabi Muhammadu (ﷺ). Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da taurari masu ɓuya kafin su bayyana da daddare, masu gudu a cikin falaƙinsu suna ɓuya lokacin hudowar hasken asuba, kamar yadda gada take ɓoyewa a cikin gidanta. Ya kuma yi rantsuwa da farkon dare lokacin da ya fuskanto, da ƙarshensa lokacin da ya ba da baya. Ya kuma yi rantsuwa da asuba yayin da haskensa ya bayyana. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi waɗannan rantse-rantse ne domin ya tabbatar da cewa, lalle Alƙur'ani da aka saukar wa Annabi Muhammadu (ﷺ) maganar Allah ce da wani amintaccen mala'ika ya isar masa da ita, watau Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya amince masa ya isar wa da Manzonsa (ﷺ) zancensa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da cewa, ma'abocin ƙarfi ne, kuma mai babban matsayi ne a wurin Ubangijin Al'arshi, watau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Kuma mala'iku a sama suna yi masa ɗa'a, kuma an aminta da shi game da saƙon wahayi da yake saukowa da shi ga Annabi (ﷺ).
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana siffar Annabi (ﷺ) da aka saukar wa Alƙur'ani, ya tabbatar wa mushirikai cewa, shi Manzon Allah (ﷺ) ne ba mahaukaci ba ne kamar yadda suke riyawa, domin sun san shi sarai sun kuma san hankalinsa da nutsuwarsa da gaskiyarsa da amanarsa.
Kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, Manzon Allah (ﷺ) ya ga Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a sararin samaniya mabayyani, kuma a cikin surarsa da Allah ya halicce shi da ita, don haka ya san mai kawo masa wahayi sarai babu wanda zai yi masa basaja. Kuma shi Manzon Allah (ﷺ) ba mai yi musu rowar abin da aka yiwo masa wahayinsa ba ne, yana isar musu da saƙon da aka umarce shi ya isar musu, kuma ba ya karɓar wani lada a wurinsu kamar yadda bokaye suke karɓa.

Sannan Allah ya sake tabbatar musu cewa, Alƙur'ani ba zancen Shaiɗani ne la'ananne ba wanda aka riga aka kore shi daga rahamar Allah.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi mushirikai cewa, ina kuma suka dosa ne wajen ci gaba da ƙaryata cewa Alƙur'ani daga Allah ne bayan sun ji wannan ƙwararan hujjoji? Ya sake tabbatar musu cewa, Alƙur'ani ba wani abu ba ne sai wa'azi da tunatarwa ga talikai, mutane da aljannu, ga wanda ya ga dama daga cikinsu ya bi hanya madaidaiciya, ya rungumi gaskiya. To amma su sani cewa ba duk abin da suka ga dama mai kyau ko mummuna ne zai auku ba sai Allah Ubangijin talikai ya ga damar aukuwarsa sannan zai auku.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da aukuwar tashin alƙiyama.

2. Lokacin tashin alƙiyama duk tsarin gudanar da duniya na sama da na ƙasa zai ruguje ya tarwatse.

3. Tabbatar da tashin matattu daga ƙaburburansu, domin tattara su a gaban Allah don sauraron hisabi da sakamako.

4. A ranar alƙiyama duk wani abu da yake ɓoye zai fito fili; kowane mutum zai fahimci irin ribar da ya ci ko asarar da ya tabka. A nan ne azzalumi zai ciji ɗan yatsa yayin da zai ga abin da ya aikata a gabansa, ya tabbatar da cewa, ya gamu da azabar da babu mai iya ƙwatar sa daga gare ta. A nan kuma masu taƙawa za su rabauta da kyakkyawan sakamakon ayyukansu, su sami ni'ima ta har abada marar yankewa.

82-Suratul Infiɗar

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Sunan da ta fi shahara da shi shi ne *'Suratul Infiɗar'*. A cikin *Sahihul Bukhari* an kira ta da '*Suratu Izas Sama'un Faɗarat'*. Watau an kira ta da kalmomin ayarta ta farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce Makkiyya babu wani saɓani.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin da biyu (82) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratun Nazi'at'* gabanin *'Suratul Inshiƙaƙ'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Adadin ayoyinta goma sha tara ne (19).

5. Falalarta:
An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda zai yi farin cikin ya ga kamar yana ganin alƙiyama ƙuru-kuru da idonsa, to ya karanta '*Izas Shamsu Kuwwirat'* da 'Izas Sama'un Faɗarat' da *'Izas Sama'un Shaƙƙat'*." [Ahmad #4806 da Tirmizi #3333].

6. Babban Jigonta:
Tana bayanin tashin alƙiyama ne yayin da manya-manyan halittu za su tarwatse.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tabbatar da tashin alƙiyama da abubuwan ban tsoro da za su faru lokacin zuwanta.

• Jan hankalin mushirikai a kan su sake duba al’amuran da suka hana su yarda da Ɗayantakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da yin imani da tashin alƙiyama.
• Tabbatar da cewa ana ƙididdige dukkan ayyukan bayi kuma za a yi musu sakayya a kansu.
• Gargaɗin mutane a kan cewa kada su yi tsammanin akwai abin da zai iya kuɓutar da su daga sakamakon munanan ayyukansu.

Suratul Infiɗar (1-5)

إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنفَطَرَتۡ ۝١ وَإِذَا ٱلۡكَوَاكِبُ ٱنتَثَرَتۡ ۝٢ وَإِذَا ٱلۡبِحَارُ فُجِّرَتۡ ۝٣ وَإِذَا ٱلۡقُبُورُ بُعۡثِرَتۡ ۝٤ عَلِمَتۡ نَفۡسٞ مَّا قَدَّمَتۡ وَأَخَّرَتۡ ۝٥إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنفَطَرَتۡ ۝١ وَإِذَا ٱلۡكَوَاكِبُ ٱنتَثَرَتۡ ۝٢ وَإِذَا ٱلۡبِحَارُ فُجِّرَتۡ ۝٣ وَإِذَا ٱلۡقُبُورُ بُعۡثِرَتۡ ۝٤ عَلِمَتۡ نَفۡسٞ مَّا قَدَّمَتۡ وَأَخَّرَتۡ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Idan sama ta tsattsage.

2. Idan kuma taurari suka farfaɗo suka tarwatse.

3. Idan kuma koguna aka harhaɗe su.

4. Idan kuma ƙaburbura aka fito da matattun da ke cikinsu.

5. Kowane rai ya san abin da ya gabatar da wanda ya jirkintar.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da ambaton wasu manyan al’amura huɗu da za su faru kafin tashin alƙiyama :
Na farko, idan sama ta tsattsage domin saukar mala’iku.
Na biyu, idan taurari suka farfaɗo, suka warwatse, watau haskensu da kyansu suka gushe.
Na uku, idan koguna aka harhaɗe su da junansu, suka gauraya suka zama kogi ɗaya.
Na huɗu, idan ƙaburbura aka bubbuɗe su aka fito da matattun cikinsu, aka tara su wuri ɗaya a gaban Allah domin yi musu hisabi.
To a wannan lokaci kowane rai zai san ayyukan da ya yi a duniya da wanda ya jinkirtar bai aikata ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin butulcin ɗan’adam kafiri, yana ganin ɗimbin ni’imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa tun daga kan halittarsa amma yana kafirce masa, yana saɓa wa umarninsa.

2. Yawan karamcin Allah ne ga bayinsa yake sanya wasu su ruɗu har su butulce wa umarninsa.

3. Kyan surar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci ɗan’adam da ita tana daga cikin ni’imominsa gare shi.

4. Karyata ranar sakamako shi ne ya sanya kafirai suka ci gaba da kafircinsu da bijire wa wa’azi da gargaɗi.

5. Duk abin da ɗan’adam yake aikatawa mai kyau da mummuna, babba da ƙarami akwai mala’iku tare da shi suna rubutawa.

Suratul Infiɗar (6-12)

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلْإِنسَـٰنُ مَا غَرَّكَ بِرَبِّكَ ٱلْكَرِيمِ ٦ ٱلَّذِى خَلَقَكَ فَسَوَّىٰكَ فَعَدَلَكَ ٧ فِىٓ أَىِّ صُورَةٍ مَّا شَآءَ رَكَّبَكَ ٨ كَلَّا بَلْ تُكَذِّبُونَ بِٱلدِّينِ ٩
وَإِنَّ عَلَيْكُمْ لَحَـٰفِظِينَ ١٠ كِرَامًا كَـٰتِبِينَ ١١ يَعْلَمُونَ مَا تَفْعَلُونَ ١٢

6. Ya kai mutum, me ya ruɗe ka ne game da Ubangijinka Mai karamci?

7. Wanda Ya halicce ka Ya kuma daidaita ka Ya miƙar da kai?

8. Ya harhaɗa ka cikin irin surar da Ya ga dama?

9. A'a dai, kawai dai kuna ƙaryata ranar sakamako ne.

10. Kuma lalle akwai masu kula da ku.

11. Masu daraja marubuta.

12. Suna sane da abin da kuke aikatawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira ɗan'adam ya ja hankalinsa game da sakacinsa wajen bautar Ubangijinsa, ya tambaye shi cewa, mene ne ya ruɗe shi game da Ubangijinsa mai karamci, har yake saɓa wa umarninsa, duk kuwa da ya saurara masa bai gaggauto masa da uƙuba ba?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa duk wani mai girman kai da saɓon sa cewa, ya sani Allah ne ya halicce shi bayan a da babu shi, sa’annan ya daidaita masa gaɓoɓinsa, ya miƙar masa da halittarsa ya yi matuƙar kyau. Sannan a duk cikin irin surar da ya ga damar halittar sa hakan ya halicce shi, watau ya lura da babbar ni’imar da ya yi masa yayin da bai yi masa irin halittar jaki ba ko ta biri ko ta kare.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar wa kafirai masu ruɗuwa da duniya cewa, al’amarin ba kamar yadda suka ɗauka ba ne, suna dai kawai ƙaryata ranar sakamako ne, sun ƙi yin imani da zuwanta, amma su sani dole sai ta zo, an kuma yi musu hisabi a kan ayyukansu, domin kuwa koyaushe akwai mala’iku masana marubuta tare da su suna kiyaye dukkan ayyukansu, suna rubuta su ba tare da sun bar komai ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa muminai masu yi masa biyayya alƙawarin rayuwa cikin ni’ima, wannan bai taƙaita a lahira kaɗai ba; yana hore musu ni’imarsa tun a duniya, ya sa musu nutsuwar zuciya da kwanciyar hankali da wadatar zuci; yana kuma ni’imta su har a rayuwarsu ta ƙabari, sannan uwa-uba ga rayuwar ni’imar Aaljanna da ganin Fuskarsa mai girma.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa da fajirai waɗanda suka bijire wa dokokinsa da alƙawarin jefa rayuwarsu cikin azaba, wannan bai taƙaita a lahira kaɗai ba tun ma a nan duniya suna rayuwa ne ta ƙunci da damuwa da ɗimuwa da rashin nutsuwar zuci, sannan za su gamu da ƙuncin rayuwar ƙabari da azabarsa, sannan kuma uwa-uba idan sun je lahira su gamu da azaba madawwamiya a wutar Jahannama mai tsananin ƙuna.

3. Ranar alƙiyama rana ce da mulkin Allah kaɗai zai bayyana ga kowa da komai, babu wani wanda zai mallaki ta cewa, a ranar sai dai abin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya so ya yi umarni da shi.

Suratul Infiɗar (13-19)

إِنَّ ٱلۡأَبۡرَارَ لَفِي نَعِيمٖ ١٣ وَإِنَّ ٱلۡفُجَّارَ لَفِي جَحِيمٖ ١٤ يَصۡلَوۡنَهَا يَوۡمَ ٱلدِّينِ ١٥ وَمَا هُمۡ عَنۡهَا بِغَآئِبِينَ ١٦ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلدِّينِ ١٧ ثُمَّ مَآ أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلدِّينِ ١٨ يَوۡمَ لَا تَمۡلِكُ نَفۡسٞ لِّنَفۡسٖ شَيۡـٔٗاۖ وَٱلۡأَمۡرُ يَوۡمَئِذٖ لِّلَّهِ ١٩

13. Lalle mutanen kirki tabbas suna cikin ni’ima

14. Lalle kuma fajirai tabbas suna cikin (wutar) Jahima.

15. Za su ƙonu da ita ranar sakamako.

16. Kuma su ba masu rabuwa ne da ita ba.

17. Kuma kai me ya sanar da kai mece ce ranar sakamako?

18. Sannan me ya sanar da kai mece ce ranar sakamako?

19. (Ita ce) ranar da wani rai ba ya mallakar wani amfani ga wani rai; al’amari kuwa (gaba ɗayansa) a wannan ranar yana ga Allah.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana karkasuwar mutane a lahira gida biyu ; mutanen kirki waɗanda suka kula da haƙƙoƙin Allah da haƙƙoƙin bayinsa, suka yawaita ayyukan alheri, to waɗannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar cewa lalle suna cikin ni’ima madawwamiya a ranar alƙiyama. Sai kuma fajirai waɗanda suka yi watsi da haƙƙoƙin Allah da na bayinsa, suka aikata munanan ayyuka, waɗannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, lalle suna cikin wutar Jahima, za su shige ta a ranar sakamako su ɗanɗani matsanancin zafinta; idan kuma sun riga sun shige ta, to ba za su taɓa barin ta ba har abada, za su dawwama ne a cikinta.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Manzonsa (ﷺ) girman wannan rana ta alƙiyama, yana mai nanata masa tambayar cewa, mene ne ya sanar da shi abin da ake kira ranar sakamako? Sai kuma ya amsa masa da kansa cewa, ita ce ranar da wani mutum ba zai iya amfanar da wani da komai ba; al’amura gaba ɗayansu a ranar ga Allah suke shi kaɗai; shi ne zai yi yadda ya ga dama da kowa, babu mai iya hana shi aikata abin da ya so.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haɗama a harkar kasuwanci mummunar ɗabi’a ce, babu mai kuɓuta daga gare ta sai mai tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Buɗe Surar da ambaton narkon azaba yana nuna haɗarin wannan aiki, babu shakka ha'inci abu ne mai haɗari a harkar kasuwanci da tattalin arziki na duniya, domin awo da ma’auni da sikeli muhimmin al’amari ne a harkar kasuwanci da tattalin arziki. Duk wata matsala ta rashin gaskiya da za ta shiga ciki sai ta haifar da wata matsala babba a sha’anin kasuwanci.

3. Kamar yadda mutum yake son ya karɓi haƙƙoƙinsa cikakku a wurin mutane, to hakanan wajibi ne a kansa shi ma ya ba su duk haƙƙoƙinsu cikakku waɗanda suka danganci dukiya ko mu'amala ta yau da gobe.

4. Tuna tsorace-tsoracen ranar alƙiyama zai hana mutum faɗawa cikin saɓon Allah ko cutar da mutane.

83-Suratul Muɗaffifin

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da *'Suratul Muɗaffifin'*. Amma a cikin waɗansu littattafan hadisi an kira ta da '*Suratu Wailun Lil Muɗaffifin'*, watau an yi mata sunan da ayarta ta farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
An yi saɓani game da inda aka saukar da ita; wasu magabata suna ganin Sura ce *Makkiyya,* kamar yadda aka ruwaito a wasu ruwayoyi daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda). Wannan kuma shi ne ra'ayin Abdullahi ɗan Zubair (Allah ya ƙara masa yarda) da Katada da Zuhri da Aliyyu ɗan Ɗalha.
Wasu kuma suna ganin *Madaniyya* ce, kamar yadda aka ruwaito daga Aliyyu ɗan Husain da Ikrimah da Alhassan Albasri da Suddi da Muƙatil da wata ruwaya daga Ibnu Abbas (Allah ya ƙara masa yarda).
Akwai masu ganin farkonta Madani ne, sauranta kuma *Makki* ne.
Wasu kuma suna ganin ta sauka ne tsakanin Makka da Madina.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin da shida (86) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Ankabut'* kafin '*Suratul Baƙara'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta talatin da tara ne (39) daidai.

5. Dalilin Saukarta:

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da Annabi (ﷺ) ya zo Madina ya same su sun fi kowa rashin kyautata ma'auni, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan Sura, sai suka gyara ma'auninsu daga sannan." [Ibn Maja #2223 da Ibn Hibban #4919 da Hakim #2240].
Wannan yana daga cikin dalilan masu cewa Sura ce *Madaniyya*.

6. Babban Jigonta:
Tana magana ne game da halayen mutane dangane da awo da mudu ko sikeli da tsoratar da su game da tauye haƙƙoƙin mutane da sakamakon marasa gaskiya da masu gaskiya a ranar alƙiyama.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Gargaɗi da tsoratarwa game da tauye mudu da sikeli.
• Tabbatar da tsayuwa a gaban Allah a ranar alƙiyama domin yin hisabi.
• Narko ga masu ƙaryata ranar sakamako da ƙaryata kasancewar Alƙur'ani saukakke ne daga Allah.
• Bayanin kyakkyawan sakamako na mutanen kirki a ranar alƙiyama da ɗaukakar matsayinsu da darajarsu a wurin Allah da mala'ikunsa.
• Bayanin izgili da shaƙiyanci da mushirikai suke yi wa muminai masu rauni a nan duniya da yadda reshe zai juye da mujiya a ranar alƙiyama, muminai su riƙa yi wa mushirikai dariya yayin da za su gan su a cikin azaba da wulaƙanci.

Suratul Muɗaffifin (1-6)
وَيۡلٞ لِّلۡمُطَفِّفِينَ ١ ٱلَّذِينَ إِذَا ٱكۡتَالُواْ عَلَى ٱلنَّاسِ يَسۡتَوۡفُونَ ٢ وَإِذَا كَالُوهُمۡ أَو وَّزَنُوهُمۡ يُخۡسِرُونَ ٣ أَلَا يَظُنُّ أُوْلَٰٓئِكَ أَنَّهُم مَّبۡعُوثُونَ ٤ لِيَوۡمٍ عَظِيمٖ ٥ يَوۡمَ يَقُومُ ٱلنَّاسُ لِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Tsananin azaba ya tabbata ga masu tauye ma'auni.

2. Waɗanda idan suka auna daga wajen mutane suna cikawa fal.

3. Idan kuwa su za su aunar, da mudu ne ko da sikeli, to sai su tauye.

4. Yanzu waɗannan ba sa zaton cewa su lalle za a tashe su?

5. A wata rana mai girma?

6. Ranar da mutane za su tsaya gaban Ubangijin talikai?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da kakkausan alƙawarin narko da azaba ga masu tauye ma'auni. Ya bayyana su da cewa, su ne waɗanda idan suka yi awo daga wasu sai sun cika ma'aunai fal, ba sa rage haƙƙinsu ko kaɗan. Amma kuma idan su ne za su auna wa mutane da mudu ko da sikeli sai su tauye musu haƙƙoƙinsu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin waɗannan mutane tare da tsoratarwa cewa, wai hala ba su tabbatar da cewa, za a tashe su ba a wata rana mai girma, watau ranar alƙiyama, ranar da duk mutane za su tsaya a gaban Ubangijin halittu domin yi musu hisabi da sakamako a kan ayyukansu?

An karƀo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya umarci Siba'u ɗan Urfu (Allah ya ƙara masa yarda) ya kula da garin Madina yayin da ya fita zuwa Khaibara, sai Siba'u ya karanta wannan Surar, sai na ce (in ji Abu Huraira): "Wane kuwa ya hallaka, domin yana da sa'i biyu, ɗaya yana aunarwa da shi, ɗayan kuma yana auna da shi." [Ahmad #8552 da Al-Hakim #2241 da Albazzar #8140].

An karƀo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda), ya karanta wannan ayar sai ya fashe da kuka ya ce: "Shi ne mutumin da zai ɗau wani aiki, ko wani mai yin awo alhalin ya san yana tauye wa mutane kayan awonsu, to laifinsa yana kan wanda ya ba shi aikin." [Al-Hakim, juzu'i na 2, shafi na 517].

An karƀo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Abubuwa biyar sakamako ne na abubuwa biyar." Sahabbai suka ce: "Me ake nufi da abu biyar sakamakon abu biyar ne?" Sai ya ce: "Babu mutane da za su riƙa warware yarjejeniya sai an bai wa maƙiyansu nasara a kansu. Kuma ba za su koma yin hukunci da abin da ba shi Allah ya saukar ba sai talauci ya yaɗu a tsakaninsu. Kuma alfasha ba za ta bayyana a cikinsu ba sai mace-mace sun yaɗu a cikinsu. Ba kuma za su tauye ma'auni ba sai an hana musu amfanin gona an jarrabe su da fari. Ba za su kuma hana zakka ba sai an hana su ruwan sama." [Aɗɗabrani #10992].

An karƀo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya karanta faɗar Allah: (*Ranar da mutane za su tsaya a gaban Ubangijin talikai*) sai ya ce: "Har sai ɗayansu ya nutse a cikin guminsa wanda zai kai har daidai kunnuwansa." [Bukhari #4938 da Muslim #2862].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayanin matabbatar ayyukan kafirai da munafukai da fasiƙai.

2. Ketare iyakokin Allah da yawan aikata laifuka su suka sanya kafirai ƙaryata ranar alƙiyama. Amma wanda yake son gaskiya yake kuma ƙaunar ya ga an yi adalci, yana kula da dokokin Allah, wannan ba zai taƀa ƙaryata ranar sakamako ba, domin ya ga dalilai ƙwarara masu tabbatar da zuwanta.

Suratul Muɗaffifin (7-13)
كَلَّآ إِنَّ كِتَٰبَ ٱلۡفُجَّارِ لَفِي سِجِّينٖ ۝٧ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا سِجِّينٞ ۝٨ كِتَٰبٞ مَّرۡقُومٞ ۝٩ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ۝١٠ ٱلَّذِينَ يُكَذِّبُونَ بِيَوۡمِ ٱلدِّينِ ۝١١
وَمَا يُكَذِّبُ بِهِۦٓ إِلَّا كُلُّ مُعۡتَدٍ أَثِيمٍ ۝١٢ إِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِ ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ۝١٣

7. Tabbas, lalle littafin fajirai yana cikin *Sijjinu*.

8. Me kuma ya sanar da kai me ake ce wa *Sijjinu*?.

9. Littafi ne rubutacce.

10. Tsananin azaba a wannan ranar ya tabbata ga masu ƙaryatawa.

11. Waɗanda suke ƙaryata ranar sakamako.

12. Babu kuwa mai ƙaryata ta sai duk wani mai shisshigi mai yawan saƀo.

13. Idan ana karanta masa ayoyinmu sai ya ce: "Wannan tatsuniyoyi ne na mutanen farko."

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa masu ƙaryata ranar alƙiyama cewa, abin ba kamar yadda suke tsammani ne ba, domin kuwa dukkan ayyukan bayi suna nan a rubuce, kuma tabbas littafin fajirai daga cikin kafirai da munafukai yana cikin *Sijjinu*, watau a can ƙarƙashin ƙasa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, mene ne ya sanar da shi abin da ake kira *Sijjinu*? Sai ya bayyana masa shi da cewa, wani rubutaccen littafi ne wanda ya ƙunshi cikakkun ayyukan fajirai cif-cif babu daɗi babu ragi..

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle bawa kafiri idan ya zo barin duniya zai fuskanci lahira, sai wasu mala’iku masu baƙaƙen fuskoki su sauko masa daga sama da wata algarara a tare da su, su zauna a gabansa iya ganinsa, sannan Mala’ikan mutuwa ya zo ya zauna daidai kansa sannan ya ce: “Ya kai wannan mummunan rai, ka fito zuwa ga hushin Ubangijinka” sai (ran) ya warwatsu a jikinsa, sai Mala’ikan mutuwa ya fizgo shi kamar yadda ake fizgo da ƙarfen gashin nama daga jiƙaƙken gashin dabbobi, sai ya cabke shi; yana cabkar sa, sauran mala'ikun ba za su bar shi a hannunsa daidai da ƙiftawar ido ba har sai sun saka shi cikin wannan algararar, sai ya fito daga cikinta yana wari kamar mushen da ya fi kowane irin mushe wari a bayan ƙasa, sai su hau sama da shi, duk sanda suka wuce ta gaban wata jama’a ta mala’iku sai sun ce: “Wane mummunan rai ne wannan?” Sai su ce: “Wane ne ɗan wane.” Su kira shi da mafi munin sunan da ake kiran sa da shi a duniya, har sai sun isa sama ta farko da shi, sai a nemi a buɗe masa, sai a ƙi buɗe masa.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya karanta faɗar Allah: “*Lalle waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, kuma suka yi girman kai gare su, ba za a buɗe musu ƙofofin sama ba, ba kuma za su shiga Aljanna ba har sai raƙumi ya shige ta ƙofar allura*.” Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: “Ku rubuta littafinsa a cikin *Sijjinu,* a can ƙasa ta ƙarshe.” Sai a jefo ransa ƙasa da ƙarfi….” [Ahmad #18534].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake jan kunnen masu ƙaryata ranar alƙiyama, ya yi musu alƙawarin narkon azaba da asara a wannan ranar da cewa, babu mai ƙaryata wannan ranar ta alƙiyama sai mutumin da ya zamanto mai yawan ƙetare iyakar Allah, mai yawan aikata laifuka; idan ana yi masa wa’azi ana karanta masa ayoyin Allah da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) sai ya ƙaryata su, ya ma ce, duk tatsuniyoyin mutanen da ne ba daga Allah suke ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Munin haɗarin zunubai ga zukata, domin sukan sa zuciya ta yi tsatsa har tsatsar ta lulluɓe ta gaba ɗaya ta dusashe haskenta ta kashe ta murus, daga nan sai ta riƙa ganin gaskiya a matsayin ƙarya, ƙarya kuma ta zamo ita ce gaskiya a wurinta. Wannan shi ne babban haɗarin zunubai.

2. Tabbatar da ganin Allah a lahira ga muminai, kamar yadda hadisai na Annabi da dama suka tabbatar.

3. Sakamako gwargwadon jinsin laifi ne, domin kamar yadda kafirai a duniya suka rufe idanuwansu suka ƙi ganin gaskiya, to hakanan a lahira za a hana musu ganin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Muɗaffifin (14-17)
كَلَّا ۖ بَلْ ۜ رَانَ عَلَىٰ قُلُوبِهِم مَّا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ﴿١٤﴾ كَلَّآ إِنَّهُمْ عَن رَّبِّهِمْ يَوْمَئِذٍ لَّمَحْجُوبُونَ ﴿١٥﴾ ثُمَّ إِنَّهُمْ لَصَالُوا۟ ٱلْجَحِيمِ ﴿١٦﴾ ثُمَّ يُقَالُ هَٰذَا ٱلَّذِى كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ﴿١٧﴾

14. A'a, abin ai ba haka ba ne; abin da suke aikatawa ne ya yi tsatsa a zukatansu.

15. Tabbas! Lalle su haƙiƙa ababan kangewa ne daga (ganin) Ubangijinsu a wannan rana.

16. Sannan kuma lalle su tabbas masu shiga wutar Jahimu ne.

17. Sannan za a ce: “Wannan ne abin da kuka kasance kuna ƙaryata shi.”

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara tsawatar wa masu ƙaryata ranar alƙiyama, ya kuma tabbatar musu cewa, ba wani abu ne ya sanya su ƙaryatawa ba sai yawan laifukan da suke aikatawa, su ne suka toshe musu hankulansu don haka suka kasa ganin gaskiya da zukatansu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Haƙiƙa bawa idan ya yi wani zunubi sai a ɗiga wani baƙin ɗigo a kan zuciyarsa, idan ya tuba ya daina ya nemi gafarar Allah sai a goge masa zuciyarsa tas; idan kuwa ya koma ga wannan laifin sai wannan baƙin ɗigo ya daɗa ƙaruwa har sai ya lulluɓe zuciyarsa. Wannan ita ce tsatsar da Allah ya ambata a Alƙur’ani: “*A’a, ba haka abin yake ba, abin da suke aikatawa ne ya yi tsatsa a kan zukatansu*.” [Ahmad #7952 da Tirmizi #3624 da Ibn Maja #4244].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, a ranar alƙiyama ba su da wani matsayi a wurinsa, domin kuwa ba za a bari su gan shi ba, kamar yadda suka kasa ganin gaskiya a duniya. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, lalle su masu shiga wutar Jahima ne, su ɗanɗani kuɗar zafinta, ana daka musu tsawa da cewa, wannan azabar da suke ɗanɗana ita ce abin da suka kasance a duniya suna ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) a kanta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matabbatar ayyukan muminai, watau *Illiyyuna*.

2. Gwaggwaɓan sakamakon muminai masu biyayya a cikin gidan Aljanna.

3. Matsayin mumini mai ɗa’a ga Allah a wurin manyan mala’ikun Allah makusanta a gare shi.

4. Waiwaye zuwa ga farkon Surar, watau ma’abota duniya sun yi ta hanƙoron tattara duniya ko da ta hanyar tauye haƙƙoƙin wasu ne, don haka azabar Allah ta tabbata a gare su a ranar alƙiyama. Su kuma muminai masu ɗa’a da kiyaye haƙƙoƙin jama'a, sai suka kasance a cikin ni’imar Aljanna da abin sha mai matuƙar daɗi da ƙamshi. To a nan ne masu gasa ya dace su yi gasa, ba wajen tara abin duniya ba wanda har zai kai su ga tauye haƙƙoƙin wasu.

5. *Tasnimu* shi ne mafi darajar abin shan ‘yan Aljanna, wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mahaɗin abin shan bayinsa masu ɗa’a shi ne *Tasnimu.* Bayinsa makusanta kuwa za su sha shi ne zallansa ba tare da gauraye ba. Wannan kuwa ya faru ne saboda gwargwadon aiki gwargwadon sakamako, yayin da ayyukan bayin Allah mafiya kusanci da shi suka zama sun tsantsanta shi gare shi, sai abin shansu ya zama tsantsa babu gauraye. Amma su bayi masu ɗa’a yayin da suka gauraya ɗa’arsu da yawaita *mubahi*, sai aka gauraya musu abin shansu, watau *Tasnimu.*

Suratul Muɗaffifin (18-28)

كَلَّآ إِنَّ كِتَٰبَ ٱلۡأَبۡرَارِ لَفِي عِلِّيِّينَ ١٨ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا عِلِّيُّونَ ١٩ كِتَٰبٞ مَّرۡقُومٞ ٢٠ يَشۡهَدُهُ ٱلۡمُقَرَّبُونَ ٢١ إِنَّ ٱلۡأَبۡرَارَ لَفِي نَعِيمٍ ٢٢ عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ٢٣ تَعۡرِفُ فِي وُجُوهِهِمۡ نَضۡرَةَ ٱلنَّعِيمِ ٢٤ يُسۡقَوۡنَ مِن رَّحِيقٖ مَّخۡتُومٍ ٢٥ خِتَٰمُهُۥ مِسۡكٞۚ وَفِي ذَٰلِكَ فَلۡيَتَنَافَسِ ٱلۡمُتَنَٰفِسُونَ ٢٦ وَمِزَاجُهُۥ مِن تَسۡنِيمٍ ٢٧ عَيۡنٗا يَشۡرَبُ بِهَا ٱلۡمُقَرَّبُونَ ٢٨

18. Tabbas! Lalle littafin mutanen kirki haƙiƙa yana cikin *Illiyyuna*.

19. Me ya sanar da kai mene ne *Iliyyuna*?

20. Wani littafi ne rubutacce.

21. (Mala'iku) makusanta suke halartar sa.

22. Lalle masu biyayya tabbas suna cikin ni'ima.

23. A kan gadaje suna kallo.

24. Za ka gane hasken ni'ima a fuskokinsu.

25. Ana shayar da su giyar da aka rufe (bakin mazubinta).

26. (Har) ƙarshensa (ƙamshin) almiski ne. To game da wannan kuwa lalle masu gasa su yi gasa.

27. Mahaɗinsa kuma daga ruwan *tasnimu* yake.

28. Wani idon ruwa wanda bayi makusanta ne suke sha daga gare shi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon mutanen kirki masu yi wa Allah ɗa'a da cewa, lalle littafin kyawawan ayyukansu yana cikin *Illiyyuna*, watau wani wuri mai ɗaukaka wanda ko shi Manzon Allah (ﷺ) kansa bai san shi ba, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa shi cewa wani rubutaccen littafi ne wanda aka tanada don rubuta kyawawan ayyukan muminai, ba a rage komai daga cikinsa ko a ƙara ba, kuma mala'iku makusanta ga Allah na kowace samaniya su ne suke halartar inda yake.

An karɓo daga Bara'u ɗan Azib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Haƙiƙa bawa mumini yayin da ya zo barin duniya yana fuskantar lahira, sai wasu mala'iku masu fararen fuskoki su sauko masa daga sama, fuskokinsu suna haske kamar rana, suna ɗauke da likkafani na Aljanna da turare na Aljanna, sai su zauna a gabansa iya ganinsa, sannan Mala'ikan mutuwa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo ya zauna daidai kansa sai ya ce: "Ya kai wannan rai nutsattse, ka fito zuwa ga gafarar Allah da yardarsa." Sai (ran) ya kwararo a hankali kamar yadda ruwa yake kwararowa daga bakin gora, sai Mala'ikan mutuwa ya kama shi, daga nan sauran mala'ikun ba za su bar shi a hannunsa daidai da ƙiftawar ido ba sai sun karɓe shi sun sanya shi cikin wannan likkafanin na Aljanna, sun kuma sanya masa wannan turaren. Sai ya fito yana ƙamshin turaren almiskin da ba a taɓa jin irinsa ba a duniya. Sai mala'ikun su hau sama da wannan rai, duk sa'adda suka wuce da shi ta gaban wani taron mala'iku sai su ce: "Wane rai ne mai ƙamshi haka?" Sai mala'ikun nan su ce: "Wane ne ɗan wane." Su kira shi da mafi kyan sunan da ake kiran sa da shi a duniya, har sai sun isa sama ta farko, sai su nemi a buɗe masa, sai a buɗe musu; sai daga kowace samaniya mala'ikunta makusanta su raka shi zuwa sama ta gaba, har sai ya

kai sama ta bakwai, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ce: “Ku rubuta littafin bawana a cikin *Illiyyuna*, ku mayar da shi can ƙasa, domin ni daga ita na halicce su, kuma cikinta ne zan mayar da su, daga cikinta ne kuma zan sake tashin su karo na biyu.” [Ahmad #18534].

An karƀo daga Abu Umama (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Salla a bayan salla waɗanda babu yasasshiyar magana a tsakaninsu ana rubuta ta a cikin *Illiyyuna*.” [Abu Dawud #1288].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakonsu a ranar alƙiyama da cewa, lalle suna cikin ni’ima dawwamamma ta Aljanna, suna kan gadaje masu ado na alfarma, suna masu kallon Ubangijinsu tare da duk wani abin da zai faranta musu rai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, da a ce Manzon Allah (ﷺ) zai gan su to da ya ga fuskokinsu suna sheƙi da annuri alamar jin daɗin da suke ciki. Sannan a gefe guda kuma ga hadimansu suna shayar da su cikakken kofi na giya wanda aka rufe bakinsa, ƙamshin turaren almiski yana fita daga gare shi har zuwa ƙarshensa ba zai daina ƙamshi ba. Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya zaburar da bayinsa da cewa, game da irin wannan babban sakamako ne ya wajaba masu gasa su yi gasa ta hanyar aikata abin da Allah yake so da barin abin da ba ya so.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ƙara bayanin wannan rufaffen abin sha na ‘yan Aljanna da cewa, ana gauraya shi da wani ruwan marmaro da ake kira *‘Tasnim’*, shi kuma wani marmaro da yake can ƙololuwar Aljanna wanda bayin Allah mafiya kusanci da Allah suke shan sa tsantsa garai-garai babu haɗin komai a cikinsa, sauran muminai kuwa suna shan sa ne bayan an gauraya shi da wani abin shan daban.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yi wa masu addini izgili da kiran su da munanan sunaye sifa ce daga cikin siffofin kafirai.

2. Yana daga cikin munanan ɗabi’un maƀarnata a duniya jifan masu riƙo da gaskiya da munanan sunaye, kamar ‘masu tsattsauran ra’ayin addini’ ko ‘gidadawa’ ko ‘‘yan ta’adda’ da sauransu.

3. Tsananin ruɗuwar kafirai ba ta taƙaita ga yi wa muminai izgili ba har sai da suka haɗa da homa da farin cikin a gaban iyalansu, don su nuna musu irin bajintarsu wajen cin zarafin muminai.

4. Irin aikin mutum irin sakamakonsa a ranar alƙiyama. Wannan shi ne cikar adalcin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Muɗaffifin (29-36)
إِنَّ ٱلَّذِينَ أَجۡرَمُواْ كَانُواْ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ يَضۡحَكُونَ ٢٩ وَإِذَا مَرُّواْ بِهِمۡ يَتَغَامَزُونَ ٣٠ وَإِذَا ٱنقَلَبُوٓاْ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِمُ ٱنقَلَبُواْ فَكِهِينَ ٣١ وَإِذَا رَأَوۡهُمۡ قَالُوٓاْ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَضَآلُّونَ ٣٢ وَمَآ أُرۡسِلُواْ عَلَيۡهِمۡ حَٰفِظِينَ ٣٣ فَٱلۡيَوۡمَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنَ ٱلۡكُفَّارِ يَضۡحَكُونَ ٣٤ عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ٣٥ هَلۡ ثُوِّبَ ٱلۡكُفَّارُ مَا كَانُواْ يَفۡعَلُونَ ٣٦

29. Lalle waɗanda suka yi manyan laifuka sun kasance suna yi wa waɗanda suka yi imani dariya (a duniya).

30. Kuma idan suka wuce ta wajensu sai su riƙa zunɗen su.

31. Idan kuma sun koma wurin iyalinsu sai su komo suna masu farin ciki.

32. Kuma idan sun gan su sai su ce: “Lalle waɗannan ɓatattu ne.”

33. Ba a kuwa aiko su don su zama masu tsaron su ba.

34. To a wannan rana ne waɗanda suka yi imani za su yi wa kafirai dariya.

35. Daga kan gadaje suna kallo.

36. Shin an saka wa kafirai abin da suka kasance suna aikatawa?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda kafirai suka riƙa yi wa muminai izgili a duniya da yadda reshe zai juye da mujiya a lahira, watau su ma muminai su rama abin da kafirai suke yi musu a duniya. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, lalle masu manyan laifuka, watau kafirai sun kasance suna yi wa muminai dariya da izgilanci a duniya, idan muminai suka zo wucewa ta gabansu sai su riƙa zunɗen su, suna nuna wa junansu su da idanu, idan suka koma gidajensu wurin iyalansu sai su koma cike da farin ciki game da izgili da dariya da suka yi wa muminai, suna ganin sun yi wata bajinta, suna kuma ganin su ne masu gaskiya a kan shiriya, don haka duk sanda suka ga Musulmi sai su ce ga ɓatattu nan, watau waɗanda suka saki addinin iyaye da kakanni suka kama wani sabon addini.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, wannan shisshigi ne kawai kafirai suke yi masa da suke yin hukunci a kan wasu ba tare da wani ilimi ba, domin ba a aiko su don su zama masu tsaron ayyukan Musulmi ba har da za su riƙa faɗar wannan maganar.
Don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakonsu a lahira lokacin da su kuma muminai za su riƙa yi musu dariya kamar yadda su suka yi wa muminai dariya a duniya. A lokacin muminai za su hango kafirai suna ɗanɗanar matsananciyar azaba a wutar Jahannama su kuma suna kishingiɗe a kan gadaje na alfarma suna kallon abin da Allah ya tanadar musu na ni’ima ta har abada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, an yi wa kafirai sakayya da azaba ta wulaƙanci game da abin da suka kasance suna aikatawa a duniya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Sammai da ƙasa dukkansu masu miƙa wuya ne da biyayya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Kwaɗaitarwa game da ƙoƙari wajen kyautata aiki, domin duk wanda ya tabbatar da akwai ranar hisabi a gaban Allah, to lalle zai yi iya bakin ƙoƙarinsa ya ga ya aikata abin da za a yaba masa a wannan ranar.

3. Alamar rabauta a ranar alƙiyama ita ce karɓar littafin ayyuka ta hannun dama; alamar taɓewa kuwa ita ce karɓar sa da hannun hagu.

4. Kafiri da ya duƙufa a kan saɓon Allah da kafirci, yana yin haka ne domin ba ya jin tabbacin akwai tashi bayan mutuwa da hisabi da sakamako, wuta ko Aljanna.

84-Suratul Inshiƙaƙ

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da suna '*Suratul Inshiƙaƙ*'. An karɓo daga Abu Rafi'i (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Na yi sallar Isha a bayan Abu Huraira sai ya karanta '*Izas Sama'un Shaƙƙat*' sai ya yi sujjada. Sai na ce masa: "Wace sujjada ce wannan?" Sai ya ce: "Na yi wannan sujjadar a bayan Baban Alƙasim (ﷺ), don haka ba zan gushe ba ina yin wannan sujjadar har sai na sadu da shi." [Bukhari #768 da Muslim #578].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya,* babu wani saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tamanin da uku (83) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Infiɗar*' kafin '*Suratur Rum*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin da biyar ne (25) a lissafin mutanen Madina da Makka da Kufa, amma a lissafin mutanen Basra da Sham ashirin da uku ne (23).

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin tashin alƙiyama da yadda sama da ƙasa za su miƙa wuya su yi biyayya ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:

• Siffanta alamomin tashin alƙiyama da kasuwar mutane kashi biyu, ‘yan Aljanna da ‘yan wuta.

Suratul Inshiƙaƙ (1-15)

إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنشَقَّتۡ ۝١ وَأَذِنَتۡ لِرَبِّهَا وَحُقَّتۡ ۝٢ وَإِذَا ٱلۡأَرۡضُ مُدَّتۡ ۝٣ وَأَلۡقَتۡ مَا فِيهَا وَتَخَلَّتۡ ۝٤ وَأَذِنَتۡ لِرَبِّهَا وَحُقَّتۡ ۝٥ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡإِنسَٰنُ
إِنَّكَ كَادِحٌ إِلَىٰ رَبِّكَ كَدۡحٗا فَمُلَٰقِيهِ ۝٦ فَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ ۝٧ فَسَوۡفَ يُحَاسَبُ حِسَابٗا يَسِيرٗا ۝٨ وَيَنقَلِبُ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِۦ مَسۡرُورٗا ۝٩
وَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ وَرَآءَ ظَهۡرِهِۦ ۝١٠ فَسَوۡفَ يَدۡعُواْ ثُبُورٗا ۝١١ وَيَصۡلَىٰ سَعِيرًا ۝١٢ إِنَّهُۥ كَانَ فِيٓ أَهۡلِهِۦ مَسۡرُورًا ۝١٣ إِنَّهُۥ ظَنَّ أَن لَّن يَحُورَ ۝١٤ بَلَىٰٓۚ
إِنَّ رَبَّهُۥ كَانَ بِهِۦ بَصِيرَۢا ۝١٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Idan sama ta tsattsage.

2. Ta kuma saurari Ubangijinta, kuma ya wajaba (ta saurara).

3. Kuma idan ƙasa aka miƙe ta.

4. Ta kuma jefar da abin da yake cikinta ta wofinta.

5. Ta kuma saurari Ubangijinta kuma ya wajaba (ta saurara).

6. Ya kai mutum, lalle kai mai yin aiki ne tuƙuru zuwa ga Ubangijinka, to mai haɗuwa da Shi ne

7. To amma duk wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na dama.

8. To za a yi masa hisabi mai sauƙi.

9. Ya kuma juyo zuwa ga iyalinsa yana farin ciki.

10. Amma wanda kuwa aka bai wa littafinsa ta bayan bayansa.

11. To zai yi kiran halaka.

12. Zai kuma shiga (wutar) Sa’ira.

13. Lalle a da shi ya kasance mai farin ciki ne cikin iyalinsa.

14. Lalle ya yi zaton ba zai koma (ga Allah) ba.

15. Haka yake, (zai koma), lalle Ubangijinsa Ya kasance Mai ganin sa ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da bayanin manyan abubuwan da za su auku lokacin tashin alƙiyama, yayin da sama za ta tsattsage mala’iku su yi ta saukowa, domin ta saurari umarnin Ubangijinta ta kuma miƙa wuya gare shi, kuma haka ne ya cancanci ta yi, domin a ƙarƙashin ikonsa take, shi ne wanda ba a saɓa wa umarninsa. Ita kuma ƙasa idan Allah ya miƙar da ita kamar yadda ake miƙar da fata; taskokin da ke cikinta da matattun da suke ƙarƙashinta duka ta fito da su waje, ta rabu da su, cikinta ya

koma fayau babu sauran wani abu. A wannan lokaci ne ɗan'adam zai haɗu da Ubangijinsa domin yi masa hisabi.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kira ɗan'adam domin ya tabbatar masa da cewa, lalle shi mai aiki ne tuƙuru a nan duniya, ko dai aikin alheri ko nkuma a sharri, don haka shi mai haɗuwa ne da Ubangijinsa, don ya yi masa sakayya a kan ayyukansa masu kyau da munana.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon mutane a ranar alƙiyama gwargwadon ayyukansu da cewa, duk wanda aka ba shi littafin ayyukansa a hannunsa na dama, to wannan ya rabauta, kuma da sannu za a yi masa hisabi mai sauƙi ta hanyar bijiro ayyukansa a dunƙule ba tare da binciken ƙwaƙwaf ba. Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya suturta masa laifukansa bayan ya yi iƙirari a gabansa, sai ya juya zuwa iyalansa a Aljanna yana mai farin ciki, domin ya kuɓuta daga azabar Allah ya samu babban rabo.
Wanda kuwa aka ba shi littafin ayyukansa a hannunsa na hagu, ta bayan bayansa, to wannan zai dinga kira wa kansa hallaka, domin munin abin da ya gani rubuce a cikin littafinsa na miyagun laifukan da ya aikata a duniya bai tuba ba, kuma a ƙarshe zai shiga wutar Jahannama ya ɗandani matsanancin zafinta, domin kuwa tun a duniya sanda yake cikin iyalansa yana farin ciki da kafircinsa da saɓon Allah da yake aikatawa, ya kuma yi zaton ba za a dawo da shi da ransa bayan mutuwa ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, lalle zai mayar da shi da ransa bayan mutuwarsa kamar yadda ya halicce shi da farko, domin Ubangijinsa yana ganin duk halin da yake ciki babu abin da yake ɓuya gare shi, zai kuma yi masa sakayya a kan aikinsa.

An karɓo daga A'isha (Allah ya kara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wanda za a yi wa hisabi ne ƙeƙe-da-ƙeƙe sai ya hallaka." Sai na ce: "Shin ba Allah ne yake cewa ba: (*To duk wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na dama, to za a yi masa hisabi mai sauƙi*)?" Sai ya ce: "Wannan ba shi ne hisabin ba, wannan bijiro da ayyuka ne kawai, duk wanda za a yi masa hisabi na ƙwaƙwafi to ya hallaka." [Bukhari #103 da Muslim #2876].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya yin ranstuwa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittunsa, amma bawansa ba zai iya rantsuwa da komai ba sai da shi.

2. Jujjuyawar halin ɗan'adam daga wani yanayi zuwa wani yanayi, tun yana cikin mahaifiyarsa har zuwa mutuwarsa, babban dalili ne mai nuna cikar Kudurar Allah game da tashin matattu a ranar alƙiyama domin yi musu hisabi.

3. Akwai abin mamaki ƙwarai game da kafiran Larabawa waɗanda suke jin ana karanta musu Alƙur'ani mai cike da fasaha da azancin magana wadda su kansu sun san ta fi ƙarfin yin ɗan'adam, amma duk da haka suka ƙi miƙa wuya su sallama su gaskata annabcin Manzo (ﷺ).

4. Sakamakon muminai na Aljanna ba mai yankewa ne ba har abada.

Suratul Inshiƙaƙ (16-25)
فَلَآ أُقۡسِمُ بِٱلشَّفَقِ ١٦ وَٱلَّيۡلِ وَمَا وَسَقَ ١٧ وَٱلۡقَمَرِ إِذَا ٱتَّسَقَ ١٨ لَتَرۡكَبُنَّ طَبَقًا عَن طَبَقٖ ١٩ فَمَا لَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ٢٠ وَإِذَا قُرِئَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقُرۡءَانُ لَا يَسۡجُدُونَ۩ ٢١ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُكَذِّبُونَ ٢٢ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا يُوعُونَ ٢٣ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٢٤ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونِۭ ٢٥

16. To ina rantsuwa da shafaƙi.

17. Da kuma dare da abin da ya tattara.

18. Da kuma wata idan ya cika.

19. Tabbas za ku hau wani mataki bayan wani mataki.

20. To me ya same su ne ba sa yin imani?

21. Idan kuma an karanta musu Alƙur'ani ba sa yin sujjada?

22. A'a, su dai waɗanda suka kafirce suna ƙaryatawa ne.

23. Allah kuwa (Shi) Ya fi sanin abin da suke ɓoyewa (a zukatansu).

24. To ka yi musu albishir da azaba mai raɗaɗi.

25. Sai dai waɗanda suka yi imani, suka kuma yi ayyuka nagari, to suna da lada marar yankewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da shafaƙi, watau jan da ke bayyana a sararin samaniya bayan faɗuwar rana kafin duhu ya yi. Ya kuma rantse da dare da abin da ya tattara a cikinsa, da wata idan ya cika girmansa ya yi haske.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da waɗannan manyan halittu nasa ne don ya tabbatar wa mutane cewa, tabbas sai sun hau wani mataki bayan mataki, watau na halittarsu, sai sun kasance ɗigon maniyyi sannan su zama gudan jini sannan gudar tsoka har zuwa cikar halittarsu sannan su zo duniya su rayu har kuma zuwa mutuwarsu, daga nan kuma a tashe su don yi musu hisabi.
To wannan yanayi bayan yanayi da ɗan'adam yake shiga wata babbar hujja ce ta tabbatar da Kaɗaitakar Allah da isar Kudurarsa da cancantar a bauta masa shi kaɗai. To amma me ya samu kafirai ba sa yin imani da Kaɗaitakar Allah da ranar lahira, idan kuma aka karanta musu Alƙur'ani ba sa faɗuwa su yi wa Allah sujjada, su miƙa wuya ga umarninsa da haninsa? Maimakon haka sai dai su riƙa ƙaryata abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da shi. To su sani Allah ne mafi sanin abin da suke ɓoyewa a zukatansu, babu abin da bai sani ba na ayyukansu, don haka ya umarci Annabi (ﷺ) da ya yi musu albishir da azaba mai raɗaɗi da take tsumayin su a ranar lahira.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, amma akwai waɗanda suka yi imani da shi suka yi aiki nagari, to waɗannan suna da wani babban sakamako marar yankewa, shi ne gidan Aljanna.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittunsa. Bai halatta ga Musulmi ya yi rantsuwa ba da Allah ba.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da muminai na wannan al'umma irin tsananin azabar da muminan da suka gabace su suka sha, don ya lallashe su ya kwantar musu da hankali. Annabi (ﷺ) ya ba su labarin wannan saurayi ne, domin ya koya musu juriya da haƙuri a kan tsangwama da cutarwar da kafirai suke yi musu, su koyi haƙuri irin na wannan saurayi da jajircewa a kan gaskiya da yaɗa da'awa da shigar da mutane addinin Allah kamar yadda ya yi.

3. Allah ne mai mulkin sammai da ƙasa, duk suna ƙarƙashin ikonsa da gudanarwarsa, yana sane da komai yana jin komai yana kuma ganin komai. Don haka me ya hana masu yi wa Allah taurin kai su tsoraci damƙarsa; ko sun manta cewa dukkansu suna ƙarƙashin mulkinsa ne, kuma yana sane da ayyukansu?

85-Suratul Buruj

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Buruj*', watau da kalmar da ta zo a ayarta ta farko.

An karɓo daga Jabir ɗan Samura (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance a sallar Azahar da La'asar yana karanta '*Was-Sama'i Waɗ-Ɗariƙ*' da '*Was-Sama'i Zatil Buruj*' da surori makamantansu. [Ahmad #21018].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu wani saɓani.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ashirin da bakwai (27) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratus Shamsi*' kafin '*Suratut Tin*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin da biyu ne (22).

5. Babban Jigonta:
Tana tabbatar da ƙarfin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da ya rinjayi komai da narkonsa ga masu gallaza wa bayinsa muminai.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:

• Ba da misali ga mushirikai waɗanda suka fitini muminai da cewa, a can baya an samu irinsu waɗanda suka fitini muminai har suka tona rami suka hura wuta suka riƙa jefa su da rai a cikinta, amma haka bai sanya su sun saki addininsu ba.
• Tsananin damƙar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga azzalumai kamar yadda ya yi wa Fir'auna da Samudawa.

Suratul Buruj (1-9)
وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلۡبُرُوجِ ١ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡمَوۡعُودِ ٢ وَشَاهِدٖ وَمَشۡهُودٖ ٣ قُتِلَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأُخۡدُودِ ٤ ٱلنَّارِ ذَاتِ ٱلۡوَقُودِ ٥ إِذۡ هُمۡ عَلَيۡهَا قُعُودٞ ٦ وَهُمۡ
عَلَىٰ مَا يَفۡعَلُونَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ شُهُودٞ ٧ وَمَا نَقَمُواْ مِنۡهُمۡ إِلَّآ أَن يُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَمِيدِ ٨ ٱلَّذِي لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ
شَيۡءٖ شَهِيدٌ ٩

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da sama ma'abociyar manziloli.

2. Da ranar da aka yi alƙawarin zuwanta.

3. Da mai shaida da kuma abin yi wa shaida.

4. An la'anci ma'abota rami (na azabtar da muminai).

5. Na wuta mai ruruwa.

6. Yayin da suke zaune a gefenta.

7. Alhali su suna kallon abin da suke aikata wa muminai.

8. Babu kuwa abin da suke tuhumar su da shi sai don kawai sun yi imani da Allah Mabuwayi, Sha-yabo.

9. Wanda Yake da mulkin sammai da ƙasa. Allah kuma Mai ganin komai ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da sama ma'abociyar manzilolin rana da wata da taurari. Ya kuma rantse da ranar alƙiyama wadda ya yi alƙawarin tattara halittu a cikinta. Sannan ya rantse da duk wani mai shaida, kamar Annabi da zai ba da shaida game da al'ummarsa, da kuma duk wani abin halarta ko abin yi wa shaida.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya la'anci ma'abota wani wawakeken rami, wanda suka haƙa suka hura wuta a cikinsa ganga-ganga, suka riƙa jefa muminai a cikinsa da ransu, yayin da suke zaune a gefen ramin suna kallon yadda suke azabtar da muminai. Ba don wani laifi da suke tuhumar su da aikatawa ba, sai don kawai sun yi imani da Allah Mabuwayi, Sha-yabo, wanda shi ne kaɗai mai mulkin sammai da ƙasa, kuma mai ganin komai.
Annabi (ﷺ) ya ba da labarin waɗannan muminai da aka yi wa wannan azaba ta jefa su cikin ramin wuta, kamar yadda ya zo a hadisin da Muslim [#3005] ya ruwaito daga Suhaibu ɗan Sinan (Allah ya ƙara masa yarda) . A taƙaice hadisin ya bayyana cewa: "A da can an yi wani sarki kafiri, yana da mai yi masa aikin sihiri. To lokacin da mai sihirin ya tsufa sai ya buƙaci Sarki ya zaɓo wani matashi daga jama'arsa don ya koya masa sihiri, domin ya ci gaba da wannan aiki nasa ko bayan mutuwarsa. Sarki ya amsa masa, ya tura masa wani saurayi wanda zai riƙa koyon sihiri a wurinsa. A hanyar saurayin ta zuwa wurin

malaminsa mai sihiri sai yake gamuwa da wani malami mai ibada, ya riƙa sauraron wa’azinsa, har wa'azin ya shige shi, daga ƙarshe ya yi imani da Allah ya watsar da bautar gumakan Sarki. Lokacin da Sarki ya gano haka, sai ya sa aka kamo masa wannan malami mai ibada ya sa aka kashe shi. Ya kuma yi yunƙurin kashe wannan saurayi amma Allah bai ba shi sa’a ba. Ya bi duk hanyoyin da zai bi don hallaka shi bai yi nasara ba. Sai saurayin ya nuna masa hanya ɗaya tak wadda zai bi ya samu nasarar hallaka shi. Ita ce ya tattara mutanen gari wuri guda ya ɗauki kibiya daga cikin kwarinsa ya yi Bismilla ya ambaci sunan Allah ya harbe shi da ita. Sarki ya amince da haka. Ai kuwa yana harbin wannan yaro sai kibiyar nan ta same shi, nan take ya faɗi ya mutu. Mutanen gari na ganin haka kuwa sai duk suka fashe da sowa suna cewa: "Mun yi imani da Ubangijin yaro!" Ganin haka shi kuma Sarki sai ya sa aka haƙa wani wawakeken rami, aka hura wuta ganga-ganga a cikinsa, ya riƙa kamo muminai waɗanda suka yi imani da Allah yana jefa duk wani wanda ya ƙi ya dawo zuwa ga addininsa na bautar gumakan Sarki.
To wannan labari ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake ba wa Kuraishawa don su wa’azantu su daina cutar da Musulmi a kan addininsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Lallashin muminai da ake azabtarwa saboda addininsu da ba su tabbacin cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai yi musu ramuwar gayya a kan maƙiyansu da azabar Jahannama matuƙar ba su tuba ba kafin mutuwarsu.

2. Gwargwadon aikin mutane shi ne gwargwadon sakamakonsu a wurin Allah.

3. Karamcin Allah da haƙurinsa ga bayinsa; dubi yadda kafirai suka azabtar masa da masoyansa amma kuma yana yi musu tayin tuba don ya yafe musu.

4. An ambaci muminai mata domin a yi musu jinjina a nuna cewa, ba maza ne kaɗai suka sha wahala a kan riƙo da addininsu ba; har mata ma sun ga irin wannan taskun, irin su Sumayya mahaifiyar Ammar (Allah ya ƙara mata yarda) da Hamamatu mahaifiyar Bilal (Allah ya ƙara mata yarda) da Zinnira (Allah ya ƙara mata yarda) da sauransu.

5. Aljanna ana samun ta ne da imani da ayyuka nagari.

Suratul Buruj (10-11)
إِنَّ ٱلَّذِينَ فَتَنُواْ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ ثُمَّ لَمۡ يَتُوبُواْ فَلَهُمۡ عَذَابُ جَهَنَّمَ وَلَهُمۡ عَذَابُ ٱلۡحَرِيقِ ١٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡكَبِيرُ ١١

10. Lalle waɗanda suka azabtar da muminai maza da muminai mata sannan ba su tuba ba, to suna da azabar Jahannama, suna kuma da azabar ƙuna.

11. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Wannan kuwa shi ne babban rabo.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar wa azzalumai masu cutar da bayinsa muminai da cewa, lalle waɗanda suka fitini muminai maza da mata, suka riƙa gana musu azaba da wuta don su raba su da imaninsu, sannan ba su tuba daga zunubansu ba, to a ranar lahira suna da azabar wutar Jahannama wadda za ta ƙona su sakamakon irin azabtarwar da suka yi wa muminai ta ƙona su da wuta a duniya.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana gwaggwaɓar ni'imar da zai yi wa muminai waɗanda suka yi imani da shi suka yi kyawawan ayyuka, ya tabbatar da cewa, suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Wannan sakamako da ya tanadar musu kuwa shi ne babban rabo.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoratarwa ga kafiran Kuraishawa da suke azabtar da wasu Musulmi cewa su guji ranar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai damƙe su da azabarsa, domin damƙarsa mai tsanani ce. Sannan akwai kwantar wa muminai hankali da tabbatar musu cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba zai ƙyale azzalumai ba, ko ba daɗe ko ba jima zai damƙe su da azabarsa mai tsanani.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa kafirai azzalumai cewa su daina tsammanin sun kuɓuta daga azabar Allah, don ganin ya ƙyale su a duniya suna cin karensu babu babbaka; akwai ranar ƙin dillanci, ranar da Allah zai sake dawo musu da ransu bayan sun mutu, ya sake azabtar da su kamar yadda ya azabtar da su a duniya.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ƙaunar masoyansa ƙaunar da babu kamarta, kamar yadda babu mai kama da shi a siffofinsa da ayyukansa. Hakanan ƙaunar da masoyansa suke yi masa a zukatansu babu kamarta cikin duk abubuwan da suke nuna wa ƙauna.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa sunansa mai gafara da mai ƙauna, domin ya nuna wa bayinsa cewa, duk wanda ya yi laifi ya tuba, to zai gafarta masa, sannan ya dawo masa da ƙaunar da yake yi masa, domin Allah ya fi kowa farin cikin tuban bawansa idan ya yi laifi.

Suratul Buruj (12-16)

إِنَّ بَطۡشَ رَبِّكَ لَشَدِيدٌ ١٢ إِنَّهُۥ هُوَ يُبۡدِئُ وَيُعِيدُ ١٣ وَهُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلۡوَدُودُ ١٤ ذُو ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡمَجِيدُ ١٥ فَعَّالٞ لِّمَا يُرِيدُ ١٦

12. Lalle damƙar Ubangijinka tabbas mai tsanani ce.

13. Lalle Shi ne Yake farar (da komai) Yake kuma dawo (da shi).

14. Shi ne kuma Mai gafara, Mai ƙaunar (bayinsa na ƙwarai).

15. Ma'abocin Al'arshi Mai girma.

16. Mai aikata abin da Yake nufi.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) cewa, lalle damƙar da yake yi wa azzalumi mai tsanani ce ko da kuwa ya saurara masa na ɗan lokaci, to amma ba zai bar shi ba, domin kuwa shi ne yake farar da komai, kamar halitta da azabtar da masu laifi, sannan shi ne zai dawo da wannan halittar bayan mutuwarta, ko ya dawo da azaba a lahira ga wanda ya yi wa azaba a duniya saboda laifinsa. Kuma shi mai gafara ne ga zunuban bayinsa idan sun tuba, mai ƙaunar masoyansa ne

masu tsoron sa, kuma ma’abocin Al’arshi ne mai girma ne da karamci; yana aikata duk abin da yake nufi na ya gafarta wa wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, ko ya azabtar da wanda ya ga dama, babu mai tilasta shi a kan aikinsa (Mai tsarki da ɗaukaka).

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Labarin abubuwan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa al’ummun da suka gabata waɗanda suka ƙaryata manzanninsa, babbar shaida ce a kan gaskiyar abin da manzanninsa suka zo da shi.

2. Tsoratar da mushirikai cewa, idan ba su daina yaƙi da gaskiya ba, to su ma za su gamu da irin abin da al’ummun farko suka gamu da shi na fushin Allah da azabarsa.

3. Ba rashin samun hujjoji da ayoyi ƙarfafa suka hana kafirai yin imani ba; kawai tsaurin kai ne da bin son zuciya ya sanya su suka ci gaba da ƙaryata gaskiya.

4. Ilimin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kewaye komai da kowa.

5. Alƙur’ani tsararren littafi ne da babu mai iya gurɓata shi har abada.

Suratul Buruj (17-22)
هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلۡجُنُودِ ١٧ فِرۡعَوۡنَ وَثَمُودَ ١٨ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فِي تَكۡذِيبٖ ١٩ وَٱللَّهُ مِن وَرَآئِهِم مُّحِيطُۢ ٢٠ بَلۡ هُوَ قُرۡءَانٞ مَّجِيدٞ ٢١ فِي لَوۡحٖ مَّحۡفُوظِۭ ٢٢

17. Shin labarin runduna ya zo maka?

18. (Su ne) Fir’auna da Samudawa.

19. A'a, su dai waɗanda suka kafirta suna cikin ƙaryatawa ne.

20. Allah kuwa Yana kewaye da su (da iliminsa).

21. A'a, shi dai Alƙur’ani ne mai girma.
22. A cikin Lauhul-Mahafuzu.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana yadda ya karya rundunonin da suka haɗu don yaƙar gaskiya a can baya, inda ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, shin ko labarin rundunoni ya zo masa, watau Fir’auna da jama’arsa da Samudawa mutanen Annabi Salihu, waɗanda suka yi ganganko don faɗa da gaskiya da hana mutane karɓar ta, amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka su gaba ɗayansu.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ba rashin samun labarin waɗancan al’ummu ne ya hana waɗannan su yi imani ba; su dai kawai suna ƙaryata abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo musu da shi ne, don bin son zuciya, Allah kuwa yana kewaye da sanin duk ayyukansu, babu abin da zai ɓuya gare shi, kuma zai yi musu sakayya a kai.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya mayar musu da martani a kan da’awarsu ta cewa Alƙur’ani waƙa ce ko bokanci, da cewa, shi Alƙur’ani ne mai girma da ke cike da manyan batutuwa da alherai masu tarin

yawa da ilimi mai zurfi wanda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsare shi a cikin Lauhul Mahfuzu wanda babu mai iya canja shi ko shigar da ƙari ko ragi a cikinsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga halittunsa. Bawa ba ya halatta ya rantse da wani abu ba Allah ba.

2. Mala'iku suna tsaron ayyukan ɗan'adam masu kyau da munana, domin a yi masa hisabi a kansu ranar alƙiyama.

3. Samuwar masu tsaro a kan mutane tana nuna akwai abin da suke tsaro, watau ayyukan bayi. Tsaron ayyuka kuwa yana nuna akwai hisabi da sakamako, domin babu wata hikima a tsare ayyukan masu aiki, sannan a ƙyale su tafi a banza ba tare da wani sakamako ba. Wannan yana nuna tabbatar ranar alƙiyama wadda za a yi wa mutane sakayyar ayyukansu a cikinta.

86-Suratuɗ Ɗariƙ

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da '*Suratut Ɗariƙ'*, saboda wannan lafazin ya zo a ayarta ta farko.
An karɓo daga Jabir ɗan Samura (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance a sallar Azahar da La'asar yana karanta *'Was-Sama'i Waɗ-Ɗariƙi'* da '*Was-Sama'i Zatil Buruj'* da surori makamantansu. [Ahmad #21018].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu wani saɓani.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta talatin da shida (36), ta sauka bayan '*Suratul Balad*' kafin '*Suratul Kamar*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha bakwai ne (17).

5. Babban Jigonta:
Tana bayyana cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ne yake tsare kowa da komai, kuma yana da Kudura a kan komai, kuma shi ne mai yin hisabi ga bayinsa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:

• Tabbatar da ƙididdige ayyukan bayi da sakamakonsu.
• Tabbatar da yiwuwar tashi bayan mutuwa.
• Tunatar da ɗan’adam ingantacciyar halittar Allah da kuma hikimarsa da ke cikin halittar sa.
• Kwarzanta girman darajar Alƙur’ani.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da kwantar masa da hankali da cewa, ba da jimawa ba zai yi nasara.

Suratuɗ Ɗariƙ (1-4)

وَٱلسَّمَآءِ وَٱلطَّارِقِ ۝١ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلطَّارِقُ ۝٢ ٱلنَّجۡمُ ٱلثَّاقِبُ ۝٣ إِن كُلُّ نَفۡسٖ لَّمَّا عَلَيۡهَا حَافِظٞ ۝٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da sama da (tauraro) mai zuwa cikin dare.

2. Me ya sanar da kai mai zuwa cikin dare?

3. Tauraro ne mai keta (duhu) da haskensa.

4. Ba wani rai face akwai mai tsaron sa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da yin rantsuwa da sama da kuma tauraro mai zuwa da daddare. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, bai san mene ne mai zuwa da daddare ba, sai ya bayyana masa shi da cewa, shi ne tauraron nan mai keta duhu da haskensa mai tsananin ƙarfi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wannan rantsuwa ne domin ya tabbatar da cewa, babu wani rai face Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wakilta masa mala’ikan da yake tsaron ayyukansa, domin yi masa hisabi a kansu a ranar alƙiyama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duba a cikin halittar ɗan’adam kaɗai ya isa ya gane akwai babbar aya da take nuna girman Kudurar Allah da ikonsa a kan komai.

2. Bayanin inda ake samar da maniyyin ɗa namiji, watau tsakanin ƙashin gadon bayansa da ƙasusuwan ƙirjinsa.

3. Duk wanda ya halicci ɗan’adam daga wani wulaƙantaccen ruwa, watau maniyyi, to babu shakka yana da ikon sake dawo da shi bayan mutuwarsa.

4. Ranar alƙiyama rana ce da ake tona asirai, ake bankaɗo duk abin da zukata suka ɓoye, don haka wajibi ne ga bawa ya kyautata aƙidarsa da halayensa kafin zuwan wannan rana.

5. Ɗan’adam ba shi da wani ƙarfi ko mataimaki da zai amfane shi ranar alƙiyama, saɓanin rayuwar duniya da mutum yake tinƙaho da ƙarfinsa ko ƙarfin ƙabilarsa.

Suratuɗ Ɗariƙ (5-10)

فَلۡيَنظُرِ ٱلۡإِنسَٰنُ مِمَّ خُلِقَ ۝٥ خُلِقَ مِن مَّآءٖ دَافِقٖ ۝٦ يَخۡرُجُ مِنۢ بَيۡنِ ٱلصُّلۡبِ وَٱلتَّرَآئِبِ ۝٧ إِنَّهُۥ عَلَىٰ رَجۡعِهِۦ لَقَادِرٞ ۝٨ يَوۡمَ تُبۡلَى ٱلسَّرَآئِرُ ۝٩ فَمَا لَهُۥ مِن قُوَّةٖ وَلَا نَاصِرٖ ۝١٠

5. To mutum ya duba mana, daga me aka halicce shi?

6. An halicce shi ne daga wani ruwa mai ingizar juna.

7. Mai fita daga tsakanin tsatso da karankarma.

8. Lalle Shi (Allah) Mai iko ne a kan dawo da shi.

9. A ranar da za a bayyana asirai.

10. To ba shi da wani ƙarfi ko wani mataimaki.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci mutum da ya duba ya ga daga wane abu ne Allah ya halicce shi, don ya gane girman Kudurar Allah da gajiyawar ɗan'adam.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana masa cewa, ya halicce shi ne daga wani ruwa mai ingizar juna da ake zuba shi a cikin mahaifar mace, watau maniyyi. Wannan ruwa yana fita ne daga tsatson ɗa namiji da karankarmarsa, watau ƙashin gadon bayansa da ƙasusuwan ƙirjinsa.
Sai kuma Allah ya bayyana cewa, ashe wanda ya samar da mutum daga ruwa mai ingizar juna, lalle yana da ikon ya dawo da shi da rai bayan mutuwarsa a ranar alƙiyama, ranar da ake tona asiri, a bayyana abubuwan da suke cikin zukata na niyyoyi da aƙidu da sauransu, a tantance mai kyau da mumuna. Don haka a wannan ranar mutum ba ya da wani kataɓus ko ƙarfi da zai kare kansa da shi daga azabar Allah, kuma ba shi da wani mataimaki da zai taimake shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da sama wadda ruwa yake zubowa ta ɓangarenta. Ruwan sama kuwa shi ne mafi muhimmancin abin da mutane suke sauraron saukarsa don ganin amfanin gonarsu ya yi kyau, su kuma sami ruwan sha su da dabbobinsu. Hakanan ya rantse da ƙasa wadda ita ce wurin shuke-shukensu da samun abin rayuwarsu da ta dabbobinsu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu waɗannan rantse-rantse ne don ya nuna wa mutane muhimmancin saukar da Alƙur'ani domin ya ƙunshi duk abin da zukatansu ba za su iya rayuwa ba sai da shi; hasali ma amfaninsa a gare su ya fi amfanin ruwan sama da suke marmarin ganin saukarsa da tsirrai da suke sha'awar fitowarsu don amfaninsu.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da sama mai saukar da ruwa da ƙasa mai tsage shuka ta fito, don ya ba da misali a kan cewa shi mai iya tayar da matattu ne a ranar alƙiyama kamar yadda ya iya saukar da ruwa daga sama da fitar da tsirrai daga ƙasa.

3. Alƙur'ani littafi ne da ya yi bayanin gaskiya da ƙarya, bayani kuma daki-daki wanda kowa zai iya fahimta gwargwadon hankali da basira da Allah ya ba shi.

4. Makircin kafirai ba komai ba ne idan an gwada shi da shirin Allah, don haka muminai su kwantar da hankalinsu babu abin da maƙiyansu za su iya cutar da su da shi matuƙar suna riƙe da imaninsu.

Suratuɗ Ɗariƙ (11-17)

وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلرَّجۡعِ ١١ وَٱلۡأَرۡضِ ذَاتِ ٱلصَّدۡعِ ١٢ إِنَّهُۥ لَقَوۡلٞ فَصۡلٞ ١٣ وَمَا هُوَ بِٱلۡهَزۡلِ ١٤ إِنَّهُمۡ يَكِيدُونَ كَيۡدٗا ١٥ وَأَكِيدُ كَيۡدٗا ١٦ فَمَهِّلِ ٱلۡكَٰفِرِينَ أَمۡهِلۡهُمۡ رُوَيۡدَۢا ١٧

11. Na rantse da sama ma’abociyar dawo (da ruwa).

12. Da kuma ƙasa ma’abociyar tsagewa (shuka ta fito).

13. Lalle shi (Alƙur’ani) magana ce mai tsage gaskiya.

14. Kuma shi ba zancen banza ba ne.

15. Lalle su (kafirai) suna ƙulla mummunan makirci.

16. Ni kuma ina shirya musu mummunan sakamako.

17. To sai ka saurara wa kafirai, ka saurara musu kaɗan.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sake yin rantsuwa da sama ma’abociyar ruwa, domin ta nan yake sauka, ya sake kuma sauka. Ya kuma yi rantsuwa da ƙasa wadda take tsagewa tsirrai su fito da ‘ya’yan itatuwa da bishiyoyi.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wannan rantsuwa ne domin ya tabbatar da cewa, Alƙur’ani da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ) tabbas magana ce mai tsage gaskiya da bambance tsakaninta da ƙarya. Kuma ba wasa ko zancen banza ba ne; gaskiya ce tsantsa. To amma kafirai masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da abin da ya zo musu da shi, suna yawan shirya masa makirci domin su rusa masa da’awarsa, sai dai ba su sani ba shi ma Allah yana yi musu nasa shiri don rushe mugun nufinsu da bayyanar da gaskiya. Don haka sai ya umarci Manzonsa (ﷺ) ya ɗan saurara musu ɗan lokaci kaɗan kada ya gaggauto musu da azaba ko hallaka, da sannu ba da jimawa ba za su ga mummunan ƙarshen makircinsu, Allah kuma ya bai wa Manzonsa (ﷺ) nasara a kansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Umarni da yin tasbihi da tsarkake Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Tabbatar da ɗaukakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), ɗaukaka ta Zati da siffa da aiki.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya halicci dukkan halittunsa masu rai ya kuma daidaita halittar kowannensu gwargwadon yadda ya dace da shi, sannan ya nuna masa abin da yake maslaharsa da amfaninsa, ya kuma sanar da shi yadda zai more shi.

4. Wanda ya yi halitta ya kuma hore mata rayuwarta shi ne wanda ya cancanta a bautawa shi kaɗai.

87-Suratul A’ala

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da suna ‘Suratul A’ala’, saboda kalmar *‘Al-a’ala’* da ta zo a ayarta ta farko.
A lokacin Annabi (ﷺ) da sahabbai an fi sanin ta da ‘*Sabbihisma Rabbikal A’ala’*.
An karƀo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Mu’azu ɗan Jabal ya yi wa mutanensa sallar isha’i ya tsawaita musu karatu sai wani ɗan saurayi ya kawo ƙarar sa wurin Manzon Allah (ﷺ), sai Manzon Allah (ﷺ) ya kira shi ya ce masa: “Shin kai fitinanne ne ya Mu’azu, me zai hana ka yi musu salla da ‘*Sabbihisma Rabbika’* da ‘*Was-Shamsi Wa Dhuhaha’* da ‘*Wal-Laili Iza Yaghasha’* ?...” [Bukhari #705 da Muslim #465].

An karƀo daga Bara’u ɗan Azib (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Farkon wanda ya zo mana (watau mutanen Madina) shi ne Mus’ab ɗan Umairu da Ibn Ummi Maktum . Sun kasance suna karantar da mutane Alƙur’ani. Sai kuma Bilal da Sa’ad da Ammar ɗan Yasir (() suka iso. Sannan Umar ɗan Khaɗɗab (Allah ya kara masa yarda) ya zo tare da sahabban Manzon Allah (ﷺ) su ishirin. Sannan sai Manzon Allah (ﷺ) ya iso, ban taɓa ganin mutanen Madina sun yi farin ciki a kan wani abu ba kamar yadda suka yi farin ciki da zuwan Manzon Allah (ﷺ), har kuyangi ma sai da suka riƙa murna suna cewa: ‘Manzon Allah ya iso’. Annabi bai iso Madina ba har sai da na karanci ‘*Sabbihisma Rabbikal A’ala’* da wasu surori na ‘Al-Mufassal’. [Bukhari #3925].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance yana yin wutiri da raka'a uku, yana karanta '*Sabbihisma Rabbikal A'ala'* da '*Kul Ya Ayyuhal Kafirun' da 'Kul Huwal-Lahu Ahad*'." [Ahmad #2725 da Tirmizi #462].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin malamai. Hadisin Bara'u da ya gabata yana tabbatar da haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta takwas (8) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratut Takwir' kafin 'Suratul Laili'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha tara (19) ne babu wani saɓani a kan haka.

5. Babban Jigonta:
Surar tana tunatar da mutane ne babbar baiwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu da ƙarfafa alaƙarsu da ranar lahira da kuɓutar da su daga ƙyale-ƙyalen duniya.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tsarkake Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da Kaɗaitakarsa da bauta saboda Kaɗaitakarsa wajen halittar ɗan'adam da halittar ɗaukacin abubuwan da suke bayan ƙasa na buƙatar ɗan'adam.
• Karfafa gwiwar Manzon Allah (ﷺ) a kan karɓar wahayi daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Tabbatar wa da Manzon Allah (ﷺ) cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi shari'a mai sauƙi, ya saukar masa da littafi wanda masu tsoron Allah suke wa'azantuwa da shi suke tsarkaka da karantarwarsa. Taɓaɓɓun mutane marasa rabo kuma suke bijire masa suna fifita rayuwar duniya ƙararriya a kan ta lahira mai ɗorewa.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) game da muzgunawar da mushirikai suke yi masa da nuna masa cewa, littafin da Allah ya yi masa wahayinsa, dukkan littattafan da suka gabace shi suna gaskata shi.

Suratul A'ala (1-5)
سَبِّحِ ٱسْمَ رَبِّكَ ٱلْأَعْلَى ۝١ ٱلَّذِى خَلَقَ فَسَوَّىٰ ۝٢ وَٱلَّذِى قَدَّرَ فَهَدَىٰ ۝٣ وَٱلَّذِىٓ أَخْرَجَ ٱلْمَرْعَىٰ ۝٤ فَجَعَلَهُۥ غُثَآءً أَحْوَىٰ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ka tsarkake sunan Ubangijinka Mafi ɗaukaka.

2. Wanda Ya yi halitta sai Ya daidaita (ta).

3. Wanda kuma Ya ƙaddara (abubuwa) sannan Ya shiryar (da halittarsa).

4. Wanda kuma Ya fitar da makiyaya.

5. Sai Ya mayar da ita duddugaggiya mai baƙi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da umartar Annabi (ﷺ) da ya tsarkake Ubangijinsa mafi ɗaukaka, watau wanda yake sama da dukkan halittunsa, tare da furta sunansa lokacin ambaton sa da girmama shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta kansa da siffofi uku :
Na ɗaya, shi ne wanda ya yi halitta ya kuma daidaita halittar.
Na biyu, shi ne wanda ya ƙaddara wa kowace halitta jinsinta da nau'inta da siffofinta, ya kuma shiryar da kowane mahaluƙi zuwa ga abin da ya dace da shi.
Na uku, shi ne wanda ya fitar da abincin da dabbobi za su ci daga ƙasa, sannan ya mayar da shi duddugagge baƙi bayan da farko yana kore shar.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin karantar da Manzonsa (ﷺ) Alƙur'ani da tattara masa shi a ƙirjinsa, ta yadda ba zai manta komai ba har ya isar da shi ga al'ummarsa.

2. Annabi (ﷺ) yana iya manta wani abu na Alƙur'ani bayan isar da shi ga al'umma amma da izinin Allah. Sai dai kafin ya isar da shi, ba zai manta komai ba.

3. Annabi (ﷺ) mutum ne kamar sauran mutane, irin abubuwan da suke bijiro wa mutane na mutuntaka, kamar mantuwa da rashin lafiya sukan bijiro masa.

4. Shari'ar da Manzo (ﷺ) ya zo da ita cike take da sauƙi babu wani ƙunci a cikinta ko kaɗan.

Suratul A'ala (6-8)

سَنُقْرِئُكَ فَلَا تَنسَىٰٓ ۝٦ إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۚ إِنَّهُۥ يَعْلَمُ ٱلْجَهْرَ وَمَا يَخْفَىٰ ۝٧ وَنُيَسِّرُكَ لِلْيُسْرَىٰ ۝٨

6. Za Mu karantar da kai (Alƙur'ani) don haka ba za ka manta ba.

7. Sai abin da Allah Ya ga dama, Lalle Shi Yana sane da bayyanannen (abu) da kuma abin da yake ɓuya.

8. Kuma za Mu sauƙaƙe maka (al'umara) mafiya sauƙi

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa Manzonsa (ﷺ) babbar ni'imar da ya yi masa ta saukar masa da Alƙur'ani ya sanar da shi cewa, zai karantar da shi Alƙur'ani, ya tattara masa shi a ƙirjinsa ta yadda ba zai manta da shi ba, don haka ba sai ya yi ta bin bayan Mala'ika Jibrilu da gaggawa ba, lokacin da yake karanta masa shi don gudun kada ya manta.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi togaciyar abin da Manzonsa (ﷺ) zai iya mantawa na Alƙur'ani idan Allah ya ga damar faruwar haka, saboda wata hikima tasa, domin shi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sane da duk abin da ake bayyanawa da abin da ake ɓoyewa, babu abin da yake ɓuya a gare shi.

An karɓo daga Abdurrahman ɗan Abza (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya yi wa mutane sallar Asuba, sai ya tsallake wata aya. Yayin da ya gama salla sai ya waiwaya ya tambaya cewa: "A cikin mutanen nan akwai Ubayyu ɗan Ka'ab?" Sai Ubayyu ya ce: "Ya Manzon Allah, shin an shafe aya kaza da kaza ne ko kuma an mantar da kai ita ne?" Sai ya ce: "An mantar da ni ne." [Ahmad #5365].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) alƙawarin zai sauƙaƙe masa dukkan al'amuransa na addini da rayuwa, don ya samu damar isar da saƙon Allah cikin nutsuwa da kwanciyar hankali.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoron Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi yake sanya bawa amfanuwa da wa'azi.

2. Wutar kafiri ita ce mafi girman wuta a lahira.

3. Kafiri ba zai rayu ko ya mutu ba a wutar Jahannama.

4. Yana daga cikin ladubban bayar da ilimi guje wa sanya shi inda ba zai yi amfani ba.

Suratul A'ala (9-13)

فَذَكِّرْ إِن نَّفَعَتِ ٱلذِّكْرَىٰ ۝٩ سَيَذَّكَّرُ مَن يَخْشَىٰ ۝١٠ وَيَتَجَنَّبُهَا ٱلْأَشْقَى ۝١١ ٱلَّذِى يَصْلَى ٱلنَّارَ ٱلْكُبْرَىٰ ۝١٢ ثُمَّ لَا يَمُوتُ فِيهَا وَلَا يَحْيَىٰ ۝١٣

9. To ka yi wa'azi idan wa'azin zai yi amfani.

10. Wanda yake tsoron Allah zai wa'azantu.

11. Mafi shaƙiyanci kuma zai nesance shi.

12. Wanda zai shiga wuta mafi girma.

13. Sannan ba zai mutu a cikinta ba kuma ba zai rayu (rayuwa mai daɗi) ba.

A waɗannan ayoyi, bayan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) albishir da cewa, zai sauƙaka masa ayyukan addini waɗanda za su kai shi ga samun gidan Aljanna, sai kuma ya umarce shi da ya yi wa mutane wa'azi da Alƙur'ani, ya tunatar da su matuƙar za su saurari tunatarwarsa ta kuma amfane su. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa duk wani mai jin tsoron Allah to zai wa'azantu da wa'azinsa, amma kafiri tabaɓɓe zai guji wa'azinsa, domin ya fi kowa tsiyacewa a ranar lahira, don kuwa zai shiga wuta mafi girma ya ɗanɗani zafinta da ƙunarta, kuma ya dawwama a cikinta, ta yadda ba zai mutu ba ya huta da shan azaba, ba kuma zai yi rayuwar da zai ji daɗinta ba.

An karɓo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Amma 'yan wuta waɗanda su ne 'ya'yanta, to su ba za su mutu ba, ba kuma za su rayu ba. Sai dai akwai wasu mutane da aka sanya su wuta saboda zunubansu, sai Allah ya kashe su har su zama kamar baƙin gawayi, sai a yi izinin a yi ceto, sai a zo da su ƙungiya-ƙungiya, a baza su a kan ƙoramun Aljanna, sannan a ce: "Ya ku 'yan Aljanna, ku kwararo musu ruwan Aljanna". Sai su sake tsirowa kamar yadda ƙwayar magudanar ruwa take tsirowa." [Muslim #165].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Muhimmancin tsarkake zuciya da gaɓoɓi daga duk wani saɓon Allah.

2. An gabatar da tsarkake zuciya a kan ambaton Allah da salla, domin shi ne tushen duk wani aikin alheri, saboda duk wanda zuciyarsa ta tsarkaka to za ta haskaka da hasken shiriya, ta san abin da zai amfane ta duniya da lahira ta rungume shi.

3. Duk wanda ya fifita duniyarsa a kan lahirarsa, to lalle wannan ya nesanta kansa da samun babban rabo.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar wa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) littafi kamar yadda ya saukar wa Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) littafin Attaura.

Suratul A'ala (14-19)
قَدۡ أَفۡلَحَ مَن تَزَكَّىٰ ١٤ وَذَكَرَ ٱسۡمَ رَبِّهِۦ فَصَلَّىٰ ١٥ بَلۡ تُؤۡثِرُونَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ١٦ وَٱلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ وَأَبۡقَىٰٓ ١٧ إِنَّ هَٰذَا لَفِي ٱلصُّحُفِ ٱلۡأُولَىٰ ١٨ صُحُفِ إِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ ١٩

14. Haƙiƙa wanda ya tsarkaka ya rabauta.

15. Ya kuma ambaci sunan Ubangijinsa sannan ya yi salla.

16. Ba haka ba, ku dai kuna fifita rayuwar duniya ne.

17. Lahira kuwa ita ta fi alheri ta kuma fi wanzuwa.

18. Lalle wannan (batu) tabbas yana cikin littattafan farko.

19. Littattafan Ibrahimu da Musa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, duk wanda ya tsarkake zuciyarsa daga shirka, ya tsarkake gaɓoɓinsa daga saɓon Allah da miyagun ɗabi'u, ya kuma ambaci sunan Ubangijinsa da yin nau'ukan zikiri waɗanda Allah ya shar'anta masa, ya kuma yi salla kamar yadda aka umarce shi, to lalle wannan ya rabauta da samun gidan Aljanna da kuɓuta daga azabar lahira.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da martani ga waɗanda suka ƙi tsarkake zukatansu, suka shagaltar da kansu da bin soye-soyen zukatansu, da cewa, ba wani abu ne ya kai su ga haka ba, sai fifita rayuwar duniya a kan rayuwar lahira, tare da cewa akwai babbar tazara a tsakaninsu, domin rayuwar lahira ta fi duniya da duk abin da ke cikinta na jin daɗi, ta kuma fi ta wanzuwa, domin ni'imomin lahira ba sa yankewa har abada.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, waɗannan abubuwa da yake yi musu wa'azi da su da umarni da hani da yake yi musu, tabbas suna cikin littattafan farko da ya saukar gabanin Alƙur'ani, su ne littattafan da ya saukar wa Annabi Ibrahim (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Don haka Manzon Allah (ﷺ) bai zo musu da wani sabon abu ba wanda ya zama farau a kansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Daga cikin sunayen alƙiyama akwai *'Al-Ghashiya'*, watau mai lulluɓe mutane da tsoro.

2. Bayanin cewa, akwai wahala da gajiya a cikin wutar Jahannama, saɓanin Aljanna wadda babu wahala a cikinta sai dai hutu.

3. Sifanta abincin ‘yan wuta da ƙayar tsidau wanda ba ya sa ƙiba ba kuma ya maganin yunwa.

4. Nau’in abin shan ‘yan wuta kuwa shi ne tafasasshen ruwa mai tsananin zafi.

88-Suratul Ghashiya

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da sunan *‘Suratul Ghashiya*’ saboda lafazin *‘Al-Ghashiya*’ da ya zo a ayarta ta farko.
A littattafan hadisi an kira ta da ‘*Hal Ataka Hadisul Ghashiya*’. An karɓo daga Dhahhaƙ ɗan Kaisu, ya tambayi An-Nu’uman ɗan Bashir cewa: Me Annabi (ﷺ) yake karantawa a sallar Juma’a bayan ‘*Suratul Jumu’a’*? Sai ya ce: ‘*Hal Ataka Hadisul Ghashiya*’.” [Ahmad #18381 da Abu Dawud #1123].

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* ba tare da wani saɓani ba.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta sittin da bakwai (67) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta sauka bayan ‘*Suratuz Zariyat’* kafin ‘*Suratul Kahfi’*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin da shida ne (26).

5. Babban Jigonta:
Tana tunatar wa mutane ranar alƙiyama da abin da ta ƙunsa na ni'ima da azaba da bayanin manyan ayoyin Allah masu nuna cikar Kudurarsa a kan tashi bayan mutuwa da Kaɗaitakarsa wurin bauta.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tabbatar da aukuwar ranar alƙiyama da kasuwar mutane a cikinta gida biyu, 'yan wuta da 'yan Aljanna.
• Mayar wa Kuraishawa martani game da yiwuwar tashi bayan mutuwa wanda suke ƙaryatawa.
• Lallashin Annabi (ﷺ) game da ƙaryatawar da mushirikai suke yi masa da nuna masa cewa, shiriyarsu ba a hannunsa take ba tana hannun Allah.

Suratul Ghashiya (1-7)
هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلۡغَٰشِيَةِ ۝١ وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٍ خَٰشِعَةٌ ۝٢ عَامِلَةٞ نَّاصِبَةٞ ۝٣ تَصۡلَىٰ نَارًا حَامِيَةَۢ ۝٤ تُسۡقَىٰ مِنۡ عَيۡنٍ ءَانِيَةٖ ۝٥ لَّيۡسَ لَهُمۡ طَعَامٌ إِلَّا مِن ضَرِيعٖ ۝٦ لَّا يُسۡمِنُ وَلَا يُغۡنِي مِن جُوعٖ ۝٧

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Shin labarin mai lulluɓewa da (tsoro) ya zo maka?

2. Wasu fuskoki a wannan ranar ƙasƙantattu ne.

3. Masu aiki ne (tuƙuru) masu shan wahala.

4. Za su shiga wuta mai tsananin ƙuna.

5. Za a shayar da su daga idon ruwa mai tsananin zafi.

6. Ba su da wani abinci sai na ƙayar tsidau.

7. Ba ya sa ƙiba kuma ba ya maganin yunwa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tunatar da Manzon Allah (ﷺ) labarin ranar alƙiyama wadda take tafe babu makawa, kuma ya siffanta ta da cewa, rana ce mai lulluɓe mutane da tsoro da firgici. A wannan ranar za a tantance mutane a kasa su gida biyu, 'yan wuta da 'yan Aljanna.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta fuskokin 'yan wuta a ranar da cewa ƙasƙantattu ne, masu aiki ne tuƙuru a wutar Jahannama masu shan wahala ne matuƙa, domin za a riƙa jan su da sarƙoƙi da ƙuƙumai a wuyoyinsu har zuwa wuta mai tsananin ƙuna. Idan kuma sun buƙaci abin sha a cikinta saboda tsananin ƙishirwa sai a shayar da su wani idon ruwa mai tsananin zafi. Idan sun buƙaci abinci kuwa ba za su sami wani abinci mai ɗanɗano ba sai dai a ba su abincin da ya fi kowanne muni da azaba, watau na ƙayar tsidau, wanda ba ya sa ƙiba ba kuma ya maganin yunwa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gwaggwaɓan sakamakon mutanen kirki a lahira.

2. Duk wani mutumin kirki zai gamsu da sakamakon kyakkyawan aikinsa da za a ba shi a ranar alƙiyama, ba zai taɓa jin an yi masa ƙwange ba.

3. Gidajen Aljanna a can sama suke kuma benaye ne wani saman wani.

4. Babu wata mummunar magana a Aljanna wadda har za ta baƙanta wa wani mumini, sai dai su ji maganar aminci da kwantar da hankali.

Suratul Ghashiya (8-16)
وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ نَّاعِمَةٌ ۝٨ لِّسَعْيِهَا رَاضِيَةٌ ۝٩ فِي جَنَّةٍ عَالِيَةٍ ۝١٠ لَّا تَسْمَعُ فِيهَا لَاغِيَةً ۝١١ فِيهَا عَيْنٌ جَارِيَةٌ ۝١٢ فِيهَا سُرُرٌ مَّرْفُوعَةٌ ۝١٣ وَأَكْوَابٌ مَّوْضُوعَةٌ ۝١٤ وَنَمَارِقُ مَصْفُوفَةٌ ۝١٥ وَزَرَابِيُّ مَبْثُوثَةٌ ۝١٦

8. Waɗansu fuskokin kuwa a wannan ranar ni'imtattu ne.

9. Masu gamsuwa ne da (sakamakon) ayyukansu.

10. (Suna) cikin Aljanna maɗaukakiya.

11. Ba a jin zancen banza a cikinta.

12. A cikinta akwai marmaro mai gudana.

13. A cikinta akwai gadaje maɗaukaka.

14. Da kofuna a ajijjiye.

15. Da matasan kai a jejjere.

16. Da dardumai a shisshimfiɗe.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon 'yan Aljanna, waɗanda ya siffanta fuskokinsu da cewa masu ni'ima ne da farin ciki, saboda yalwar ni'imar da suka samu kansu a ciki, suna masu yarda da kyawawan ayyukan da suka aikata a duniya, domin su samu sakamakonsu a ninninka musu shi.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta gidajensu na Aljanna da siffofi bakwai:
Na ɗaya, Aljanna ce maɗaukakiya, watau a wurin da yake da ɗaukaka ta mahalli da ɗaukaka ta daraja da matsayi, domin gidajen Aljanna benaye ne wasu kan wasu.
Na biyu, ba sa jin wata maganar banza a cikin Aljanna ballantana su ji wata haramtacciyar magana.
Na uku, a cikinta akwai idanuwan marmaro na ruwa masu gudana waɗanda 'yan Aljanna ne da kansu suke sarrafa su bisa son ransu, ganin su kuma yake faranta musu rai.
Na huɗu, akwai gadaje maɗaukaka a cikinta, idan mumini ya zauna a kai zai ƙara hango duk ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadar musu.
Na biyar, akwai kofuna da aka ajiye don amfani da su wajen shaye-shaye, don haka ɗauka kawai za su yi yayin da suka buƙata.

Na shida, akwai matasan kai waɗanda aka jejjera a jikin juna, idan sun ga dama su zauna a kansu, idan kuma sun ga dama su jingina da su, idan sun ga dama su zauna a kan wasu su jingina da wasu.
Na bakwai, akwai shimfiɗu na alfarma da aka shimfiɗa a ko'ina don zama da hutawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk wanda yake da ƙudurar samar da manya-manyan halittu, kamar sama da ƙasa da duwatsu, to lalle yana da ikon dawo wa matattu rayukansu a karo na biyu.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin Larabawa da su yi duba zuwa ga waɗannan halittu huɗu da ya ambata, watau rakuma da sama da ƙasa da duwatsu domin kusancinsu da su, saboda kowanne ɗaya daga cikinsu yana ganin rakuminsa da yake hawa; da ya ɗaga kansa kuma zai hango sama; idan kuma ya waiwaya dama da hauni zai ga duwatsu kewaye da shi; da ya kalli ƙasansa kuma zai ga ƙasa shimfiɗe a ƙarƙashinsa. Kowane Balarabe a kullum yana ganin waɗannan halittu a tare da shi, don haka aka ja hankalinsa da ya lura da cewa, wanda ya yi irin waɗannan halittu da yake gani kullum, sake dawo da mutum bayan mutuwarsa abu ne a wurinsa mai sauƙi.

3. Rakuma wani nau'i ne na dukiyoyin Larabawa kuma abin hawansu; daga jikinsu suke samun abin da suke rayuwa da shi, suke samun nono da nama, da kuma gashinsu suke yin tufafi. Su ne suke ɗaukar musu kayayyakinsu masu nauyi daga gari zuwa gari. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa rakumi halitta mai ban al'ajabi; ya yi masa dogon wuya don ya taimaka masa wajen miƙewa tsaye yayin da aka ɗora masa kaya masu nauyi ko bayan ya tsugunna ya huta zai miƙe tsaye. Ya hore masa 'yan hanji a cikinsa waɗanda yake ajiye abinci da ruwa a cikinsu na tsawon lokaci, yadda ba zai ji yunwa ko ƙishirwa ba har tsawon kwana goma yana tafiya a sahara.

4. Larabawa suna ganin sama koyaushe, suna ganin rana da wata da taurari a sama, suna tantance hanyoyin tafiye-tafiyensu a cikin sahara ta hanyar taurari, don haka sun san girman ayar da Allah ya sanya a cikinta.

5. Duwatsu kuwa su ne wuraren zaman da dama daga cikin ƙabilun Larabawa, domin sukan yi musu amfani wajen ba su kariya daga ababan tsoro da amfani da su wajen tsaron garuruwansu.

6. Ƙasa kuwa a kanta ne suke tafiya koyaushe, a kanta ne makwancinsu da makiyayarsu da mazauninsu suke, don haka sun fi kowa fahimtar yadda aka shimfiɗa ta domin amfanin ɗan'adam.

Suratul Ghashiya (17-20)
أَفَلَا يَنظُرُونَ إِلَى ٱلْإِبِلِ كَيْفَ خُلِقَتْ ﴿١٧﴾ وَإِلَى ٱلسَّمَآءِ كَيْفَ رُفِعَتْ ﴿١٨﴾ وَإِلَى ٱلْجِبَالِ كَيْفَ نُصِبَتْ ﴿١٩﴾ وَإِلَى ٱلْأَرْضِ كَيْفَ سُطِحَتْ ﴿٢٠﴾

17. Shin ba sa duban rakumi yadda aka halicce shi?

18. Da kuma sama yadda aka ɗaga ta?

19. Da kuma duwatsu yadda aka kakkafa su?

20. Da kuma ƙasa yadda aka shimfiɗa ta?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin kafirai masu ƙaryata ranar alƙiyama da cewa, me ya sa ba za su dubi raƙuma su ga yadda aka halicce su ba, aka hore amfani da su ga ‘yanʾadam? Su kuma dubi sama su ga yadda Allah ya ɗaga ta a kansu, ta zama kamar rufi ba tare da ta faɗo a kansu ba? Su kuma dubi duwatsu su ga yadda Allah ya kafa su a cikin ƙasa, don ya hana ta tangal-tangal da mutanen da ke bayanta? Su kuma dubi ƙasa su ga yadda ya shimfiɗa ta ya sanya ta daidai da rayuwar mutane a bayanta? Watau da sun yi dubi na tsanaki zuwa ga waɗannan halittu, to da sun tabbatar da cewa, ba za su taɓa samuwa ba ba tare da mai samar da su ba, ba za su taɓa tsare kansu ba ba tare da mai tsaron su ba, da kuma lalle sun fahimci cewa, duk wanda ya yi wannan aiki yana da cikakken iko a kan dawo da matattu bayan mutuwarsu don yi musu hisabi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Babban aikin Manzon Allah (ﷺ) shi ne yi wa mutane waʾazi da tunatar da su girman Allah da hukunce-hukuncen shariʾa.

2. Aikin mai kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne isar da saƙon Allah, amma shiriya ba a hannunsa take ba tana hannun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai, shi ne yake kimsa shiriya a zuciyar wanda ya ga dama daga cikin bayinsa.

3. Babu tilastawa a shiga addini, don haka wanda ya ga dama ya yi imani wanda kuma ya ga dama ya kafirce.

4. Tabbatar da rayuwa bayan mutuwa da hisabi a kan ayyukan bayi.

Suratul Ghashiya (21-26)
فَذَكِّرۡ إِنَّمَآ أَنتَ مُذَكِّرٞ ٢١ لَّسۡتَ عَلَيۡهِم بِمُصَيۡطِرٍ ٢٢ إِلَّا مَن تَوَلَّىٰ وَكَفَرَ ٢٣ فَيُعَذِّبُهُ ٱللَّهُ ٱلۡعَذَابَ ٱلۡأَكۡبَرَ ٢٤ إِنَّ إِلَيۡنَآ إِيَابَهُمۡ ٢٥ ثُمَّ إِنَّ عَلَيۡنَا حِسَابَهُم ٢٦

21. To ka yi waʾazi, lalle kai mai waʾazi ne kawai.

22. Kai ba mai tilasta su ba ne.

23. Sai dai wanda ya ba da baya ya kuma kafirce.

24. To Allah zai azabtar da shi azaba mafi girma.

25. Lalle zuwa gare Mu ne makomarsu take.

26. Sannan kuma a kanmu ne hisabinsu yake.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lallashi Manzonsa (ﷺ) game da ƙaryata shi da mushirikai suke yi, ya umarce shi da ya yi musu waʾazi ya tsoratar da su azabar Allah da take jiran su idan ba su yi imani ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa, wannan ne kaɗai aikin da aka ɗora masa, watau ya yi musu waʾazi da tunatarwa kawai, amma ba a umarce shi sai ya tilasta su sai sun

yi imani ba, wannan aikin Allah ne ba nasa ba ne. Don haka duk wanda ya ba da baya ya bijire wa yin imani, ya kafirce wa Allah da Manzonsa (ﷺ), to wannan a ranar alƙiyama Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai azabtar da shi azaba mai girman gaske, domin kuwa zai shigar da shi wutar Jahannama inda zai dawwama a cikinta har abada.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, duk halittu gaba ɗaya makomarsu zuwa gare shi ne shi kaɗai bayan mutuwarsu, sannan shi kaɗai ne wanda ya ɗauki nauyin yi musu hisabi a kan ayyukansu da suka aikata a duniya masu kyau ko munana, babu wanda zai yi tarayya da shi a kan haka.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittarsa. Bai halatta bawa ya yi rantsuwa da komai ba sai da Allah.

2. Duk abubuwan nan da Allah ya yi rantsuwa da su abubuwa ne masu tasiri da muhimmanci a rayuwar ɗan'adam, domin sun ƙunshi lokuta masu nuna gwanintar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wajen tsara halittarsa. Ya halicci lokacin alfijir wanda ya ƙunshi ƙarshen dare da mafarar yini. Ya kuma yi dare wanda ya ƙunshi duhu zalla, kuma duk waɗannan lokuta sun ƙunshi lokutan bautar Allah da ayyukan alheri kamar kwanaki goma na farkon watan Zulhijja.

3. Falalar kwanaki goma na farkon watan Zulhijja, waɗanda su ne kwanakin da suka fi dukkan kwanakin shekara falala in ban da dararen goman ƙarshe na watan Ramadana.

89-Suratul Fajr

Mabuɗin Sura:

1.Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Fajr*'. Watau an kira ta da kalmar farko da ta zo a cikinta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu wani saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma (10) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Laili*' kafin '*Suratud Dhuha*'.

4. Adadin Ayoyinta:

Ayoyinta talatin ne (30) a lissafin mutanen Kufa da Sham. A lissafin mutanen Madina da Makka kuwa adadinsu talatin da biyu ne (32), amma a wajen mutanen Basra ishirin da tara ne (29).

5. Babban Jigonta:
Bayanin girman Kudurar Allah da halayen ɗan'adam da kuma bayanin ƙarshen masu ruɗuwa da kansu.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Ba wa mushirikai mutanen Makka misali da al'ummun Adawa da Samudawa waɗanda suka ƙaryata manzanninsu, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya hallaka su.
• Yi musu gargaɗi da azabar lahira.
• Lallashin Manzon Allah (ﷺ) da yi masa alƙawarin kawar masa da maƙiyansa.
• Rushe jiji da kan mushirikan Makka masu zaton cewa, ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu wata alama ce ta karrama su da yake yi, su kuma muminai da suke cikin talauci wata alama ce da ke nuna Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wulaƙanta su. Allah ya tabbatar musu cewa, wannan zaton banza ne ba gaskiya ba ne.
• Sukan mushirikai da nuna musu tsananin butulcinsu game da ni'imar da Allah ya yi musu, domin sun ƙi godiyar Allah a kanta, sun kuma ƙi taimaka wa raunana da ita.
• Tabbatar musu da cewa, a ranar alƙiyama za su yi nadama a kan sakaci da suka yi wajen ƙin aikata alheri a duniya, ranar da nadama ba za ta amfane su da komai ba. A ranar ne kuma muminai za su girbi amfanin alherin da suka shuka a duniya, za su rabauta da gidan Aljannar ni'ima.

Suratul Fajr (1-5)

وَٱلۡفَجۡرِ ۝١ وَلَيَالٍ عَشۡرٖ ۝٢ وَٱلشَّفۡعِ وَٱلۡوَتۡرِ ۝٣ وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَسۡرِ ۝٤ هَلۡ فِي ذَٰلِكَ قَسَمٞ لِّذِي حِجۡرٍ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da alfijir.

2. Da kuma darare goma.

3. Da kuma abin da yake cika da kuma mara.

4. Da kuma dare lokacin da yake tafiya (cikin duhu).

5. Shin a game da waɗannan akwai rantsuwa (mai gamsarwa) ga mai hankali?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da abubuwa biyar :
Na ɗaya, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya rantse da lokacin alfijir, wanda shi ne ƙarshen dare, kuma farkon gabatowar yini.
Na biyu, ya rantse da darare goma, watau kwanaki goma na farkon watan Zulhijja, kamar yadda ya zo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda), da Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda), da Abdullahi ɗan Zubair (Allah ya ƙara masa yarda), da Mujahid da Masruƙ. [Dubi, *Mausu'atut Tafsiril Ma'asur*, juzu'i na 23, shafi na 182-184].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda), ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Babu wasu kwanaki da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fi son aiki nagari a cikinsu kamar kwanaki goma (na farkon Zulhijja)". Sai aka ce: "Ya Manzon Allah, ko da jihadi don Allah?" Sai ya ce: "Ko da jihadi don Allah,

sai dai mutumin da ya fita jihadi don Allah da dukiyarsa da kansa, amma bai dawo da komai ba.” Watau ya ƙarar da dukiyarsa wajen taimakon addinin Allah, ya kuma yi shahada a fagen daga. [Bukhari #969].

Na uku, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da abu mai cika, watau abin da yake bibbiyu ko hurhuɗu ko shida-shida da sauransu.
Na huɗu, ya rantse da abin da yake mara ne, watau ɗaya ne ko uku ko biyar da sauransu.
Rantsuwa da cika da kuma mara, ta ƙunshi rantsuwa da komai cikin halittar Allah wanda yake cikin ɗayan waɗannan abubuwa biyu. Watau ko cika ne shi ko mara ne.
Na biyar, ya yi rantsuwa da dare idan ya zo ya wuce da duhunsa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da waɗannan abubuwa ne don ya tabbatar da cewa, lalle za a yi wa mutane sakayya a kan ayyukansu. Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi tambaya cewa, shin a cikin waɗannan abubuwa akwai wata rantsuwa mai gamsarwa irinta ga duk wani mai hankali? Lalle duk mai hankali zai gamsu da waɗannan rantse-rantse da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsoratar da kafirai masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) da azabar Allah, domin kuwa ya hallakar da al’ummun da suka shuɗe waɗanda sun fi su tsananin ƙarfi bayan sun ƙaryata manzanninsa. Don haka su ma ba su isa komai ba.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai taɓa halittar wata al’umma masu ƙarfi irin na Adawa ba.

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta Fir’auna da cewa ma’abocin turaku ne, domin bayyana yadda ya nuna tsanani da ƙarfi wajen azabtar da mutane da tabbatar da mulkinsa, amma duk wannan bai hana Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kawo ƙarshen mulkinsa ba, ya hallaka shi tare da rundunarsa a cikin ruwa a lokaci guda.

4. Ketare iyakokin Allah da yawan ɓarna a ƙasa ta hanyar yaɗa kafirci da saɓon Allah da zaluntar bayin Allah, yana daga cikin dalilai da suke sanya Allah ya hallaka al’umma.

5. Kashedi ga duk wani azzalumi maɓarnaci da ya sani cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana hangen duk abin da yake aikatawa, kuma zai damƙe shi a kowane lokaci, don haka duniya ta daina ruɗar sa.

Suratul Fajr (6-14)
أَلَمۡ تَرَ كَيۡفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِعَادٍ ۝٦ إِرَمَ ذَاتِ ٱلۡعِمَادِ ۝٧ ٱلَّتِي لَمۡ يُخۡلَقۡ مِثۡلُهَا فِي ٱلۡبِلَٰدِ ۝٨ وَثَمُودَ ٱلَّذِينَ جَابُواْ ٱلصَّخۡرَ بِٱلۡوَادِ ۝٩ وَفِرۡعَوۡنَ ذِي ٱلۡأَوۡتَادِ ۝١٠ ٱلَّذِينَ طَغَوۡاْ فِي ٱلۡبِلَٰدِ ۝١١ فَأَكۡثَرُواْ فِيهَا ٱلۡفَسَادَ ۝١٢ فَصَبَّ عَلَيۡهِمۡ رَبُّكَ سَوۡطَ عَذَابٍ ۝١٣ إِنَّ رَبَّكَ لَبِٱلۡمِرۡصَادِ ۝١٤

6. Shin ba ka ga yadda Ubangijinka Ya aikata ba ga Adawa?

7. (Watau ƙabilar) Iramu ma’abociyar tsawo.

8. Wadda ba a halicci irinta ba a cikin garuruwa (a tsananin ƙarfi).

9. Da kuma Samudawa waɗanda suka fafe duwatsu a wurin da ake kira *Wadil-Kura*.

10. Da kuma Fir’auna ma’abocin turaku.

11. Waɗanda suka yi ɗagawa a cikin garuruwa.

12. Suka kuma yawaita ɓarna a cikinsu.

13. Sai Ubangijinka Ya saukar musu azaba mai tsanani.

14. Lalle Ubangijinka tabbas Yana nan a madakata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya labarta wa Manzonsa (ﷺ) mummunan sakamakon da ya auka wa wasu al'ummun da suka gabata bayan sun ƙaryata annabawansu. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambaye shi cewa, shin labarin yadda ya aikata ga Adawa mutanen Annabi Hudu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) bai zo masa ba ne? Lalle labarin ya zo masa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana su da cewa, su ne ƙabilar Iramawa, watau waɗanda aka danganta su da kakansu 'Iramu', waɗanda kuma Allah ya halicce su ma'abota tsawo da ƙarfi, wadda Allah bai taɓa halittar wata ƙabila mai ƙarfinta a sauran garuruwa ba.
Allah kuma ya sake tambayar Ma'aiki (Mai tsarki da ɗaukaka) cewa, shin bai samu labarin Samudawa mutanen Annabi Salihu ba, waɗanda suka fafe duwatsu suka yi gidaje a wani wuri da ake kira Wadil-Kura? Kuma bai samu labarin Fir'auna ba, wanda yake da turaku na ɗaure mutane da gana musu azaba? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, duk waɗannan mutane sun yi taurin kai sun ƙetare iyakokin Allah a garuruwansu, domin sun yawaita ɓarna a cikinsu ta hanyar yaɗa kafirci da saɓon Allah da yaƙar Allah da manzanninsa, sai Allah ya saukar musu da azabarsa mai tsanani, ya kawar da su daga bayan ƙasa.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, lalle yana wurin da yake hangen ɗaukacin ayyukan bayinsa yake sa ido a kansu, don ya yi wa duk wanda ya kyautata aikinsa sakamako da Aljanna, ya kuma yi wa wanda ya munana aikinsa sakamako da wutar Jahannama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɗabi'ar ɗan'adam ta rashin sanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da rashin hangen nesa, yana tsammani samu da rashi su ne suke nuna yanayin dangantakar bawa da Ubangijinsa; watau idan yana son sa yana ƙaunar sa sai ya wadata shi da dukiya ko 'ya'ya ko matsayi; idan kuma ba ya son sa sai ya wulaƙanta shi ya hana shi samun wadata. Wannan mummunan zato ne na wanda bai san hikimar Allah wajen bayar da wadata ko hanawa ba, wanda kuwa Allah yana yin kowane ɗaya ne don jarrabar bawansa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana jarrabar bawa da ni'ima kamar yadda yake jarrabar sa da ƙunci.

3. Umarni da kwaɗaitarwa game da girmama maraya da taimaka masa.

4. Haɗarin cin dukiyar masu rauni cikin al'umma, don ganin ba su da wanda zai ƙwato musu haƙƙinsu.

5. Tsananin son tara dukiya yakan jefa mutum cikin miyagun aƙidu da neman dukiya ta haramtattun hanyoyi.

Suratul Fajr (15-20)

فَأَمَّا ٱلۡإِنسَٰنُ إِذَا مَا ٱبۡتَلَىٰهُ رَبُّهُۥ فَأَكۡرَمَهُۥ وَنَعَّمَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّيٓ أَكۡرَمَنِ ١٥ وَأَمَّآ إِذَا مَا ٱبۡتَلَىٰهُ فَقَدَرَ عَلَيۡهِ رِزۡقَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّيٓ أَهَٰنَنِ ١٦ كَلَّاۖ
بَل لَّا تُكۡرِمُونَ ٱلۡيَتِيمَ ١٧ وَلَا تَحَٰٓضُّونَ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلۡمِسۡكِينِ ١٨ وَتَأۡكُلُونَ ٱلتُّرَاثَ أَكۡلٗا لَّمّٗا ١٩ وَتُحِبُّونَ ٱلۡمَالَ حُبّٗا جَمّٗا ٢٠

15. Amma kuma mutum idan Ubangijinsa Ya jarrabe shi sai Ya karrama shi, Ya kuma yi masa ni’ima, sai ya ce: “Ubangijina Ya karrama ni.”

16. Amma kuma idan Ya jarrabe shi sai Ya ƙuntata masa a arzikinsa, sai ya ce: “Ubangijina Ya wulaƙanta ni.”

17. Faufau, ba haka ba ne; ku ba kwa karrama maraya ne.

18. Kuma ba kwa kwaɗaitar da juna kan ciyar da miskinai.

19. Kuma kuna cinye dukiyar gadon marayu mummunan ci.

20. Kuma kuna son dukiya so mai yawa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wani mummunan hali na ɗan’adam da rashin godiyarsa ga Allah idan ya yi masa wata ni’ima, da rashin dangana da haƙuri idan ya rasa wata ni’ima. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, lalle shi ɗan’adam idan Ubangijinsa ya jarrabe shi ya karrama shi, ya yi masa dangogin ni’ima ta dukiya da ‘ya’ya da matsayi, sai ya yi zaton wannan wata karama ce Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa don ya cancanci haka, har ya riƙa taƙama yana hura hanci yana cewa, Allah ya yi masa karamci don yana ƙaunar sa.
Hakanan kuma idan akasin haka ya faru da shi, watau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya jarrabe shi ya ƙuntata masa arzikinsa, sai ya riƙa zaton Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wulaƙanta shi, sai ya yi ta raki yana ta ƙorafi da haka.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar masa da martani, ya nuna masa kuskuren wannan mummunan zato da yake yi na cewa, samun wadata shi ne alamar ƙaunar Allah gare shi; rashi kuma shi ne alamar Allah ya wulaƙanta shi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da haɗamar masu irin wannan mummunan zato, domin ko da ya ba su dukiyar ba sa tallafa wa maraya da dukiyar da ya ba su, ba ma sa kwaɗaitar da junansu a kan ciyar da mabuƙaci wanda ba shi da cin yau balle na gobe. Tare da wannan duka suna yin rub-da-ciki a kan haƙƙoƙin raunana, kamar mata da marayu, suna cinye musu dukiyoyinsu mummunan ci. Ga su kuma da mugun son dukiya, don haka suke rowa ba sa ciyar da dukiyoyinsu don Allah.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tsananin razana na ranar alƙiyama saboda rugujewar tsarin manyar halittu, kamar sama da ƙasa da duwatsu domin zuwanta.

2. Tabbatar da cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai zo ranar alƙiyama don yi wa bayinsa hisabi, zuwa irin wanda ya dace da shi ba tare da kwatance ko kamanceceniya da na wani mahaluƙi ba.

3. Bijiro da wutar Jahannama ga kafirai a ranar alƙiyama tun kafin a jefa su cikinta, don ƙara musu razana da tsoro da tashin hankali.

4. Duk tsananin azaba ta duniya ba ta kai azabar Allah ta lahira ba, don haka bawa ya guje ta da kyawawan ayyuka tun a nan duniya.

5. Duk wani kafiri a lahira sai ya yi nadama da da-na-sani game da abin da ya aikata na kafirci da rashin yin ayyuka nagari, ranar da hakan ba zai amfana masa komai ba.

6. Mumini zai fara gamuwa da albishir tun a nan duniya lokacin da ya zo mutuwa har zuwa lokacin shigarsa Aljanna.

Suratul Fajr (21-30)

كَلَّآ إِذَا دُكَّتِ ٱلۡأَرۡضُ دَكّٗا دَكّٗا ٢١ وَجَآءَ رَبُّكَ وَٱلۡمَلَكُ صَفّٗا صَفّٗا ٢٢ وَجِاْيٓءَ يَوۡمَئِذِۭ بِجَهَنَّمَۚ يَوۡمَئِذٖ يَتَذَكَّرُ ٱلۡإِنسَٰنُ وَأَنَّىٰ لَهُ ٱلذِّكۡرَىٰ ٢٣ يَقُولُ يَٰلَيۡتَنِي قَدَّمۡتُ لِحَيَاتِي ٢٤ فَيَوۡمَئِذٖ لَّا يُعَذِّبُ عَذَابَهُۥٓ أَحَدٞ ٢٥ وَلَا يُوثِقُ وَثَاقَهُۥٓ أَحَدٞ ٢٦ يَٰٓأَيَّتُهَا ٱلنَّفۡسُ ٱلۡمُطۡمَئِنَّةُ ٢٧ ٱرۡجِعِيٓ إِلَىٰ رَبِّكِ رَاضِيَةٗ مَّرۡضِيَّةٗ ٢٨ فَٱدۡخُلِي فِي عِبَٰدِي ٢٩ وَٱدۡخُلِي جَنَّتِي ٣٠

21. Ba haka ne ba, idan aka girgiza ƙasa matuƙar girgiza.

22. Ubangijinka kuma Ya zo tare da mala’iku sahu-sahu.

23. Aka kuma zo da Jahannama a wannan ranar. To fa a wannan ranar ne mutum zai tuna (sakacinsa), ta yaya wannan tunawar za ta yi masa amfani?

24. Zai ce: “Kaitona, ina ma da na gabatar (da ayyukan alheri) a rayuwata!”

25. To a wannan ranar ba wani ɗaya da zai yi azaba irin azabarsa (watau Allah).

26. Ba kuma ɗaya da zai yi ɗauri irin ɗaurinsa.

27. (Za a ce): Ya kai wannan rai mai nutsuwa.

28. Ka koma zuwa ga Ubangijinka kana mai yarda (da sakamako), abin yarda.

29. Don haka ka shiga cikin bayina.30. Ka kuma shiga Aljannata.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin mutane game da ranar alƙiyama wadda yin tanadi dominta shi ne abu mafi amfani a gare su ba wai tara dukiya ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar musu da cewa, ba haka ya kamata aikinsu ya kasance ba, su tuna lokacin da za a girgiza ƙasa matuƙar girgiza, Allah kuma ya zo don yin hukunci tsakanin bayinsa, da mala’iku sahu-sahu. Aka kuma zo da wutar Jahannama a ranar da linzamanta har dubu saba’in, kowane linzami mala’ika dubu saba’in ne suke jan sa.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas’ud (Allah ya ƙara masa yarda), ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “A ranar alƙiyama za a zo da Jahannama tana da linzami dubu saba’in, tare da kowane linzami mala’ika dubu saba’in ne suke janye da shi.” [Muslim #2842].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a ranar ne mutum zai tuna sakacin da ya yi wajen bin Allah, amma ina wannan tunawar za ta amfane shi a wannan ranar, domin wannan ranar sakamako ce ba ranar aiki ba.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a wannan ranar ɗan'adam cikin nadama zai riƙa faɗin ina ma da ya yi wani kyakkyawan aiki domin rayuwarsa ta lahira.

An karɓo daga Muhammad ɗan Abu Umaira (Allah ya ƙara masa yarda), ɗaya daga cikin sahabban Annabi (ﷺ) ya ce: "Da a ce bawa tun sanda aka haife shi har zuwa mutuwarsa ya faɗi a kan fuskarsa (watau ya yi sujjada) har ya tsufa a cikin yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ɗa'a, to da lalle ya raina aikinsa a wannan ranar, da ya yi burin a mayar da shi duniya domin ya ƙara aikin lada." [Ahmad #17650].

A wannan ranar babu wanda zai iya yin azaba kamar azabar Allah, domin azabarsa ta fi tsanani ta kuma fi wanzuwa. Kuma babu wanda zai iya yin ɗauri da sarƙoƙi kamar ɗaurinsa ga kafirai, domin za a ɗaure su da sarƙoƙi na wuta, a ja su a kan fuskokinsu zuwa wuta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon mumini wanda tun lokacin mutuwarsa da kuma a ranar alƙiyama za a kira shi da sunan 'rai mai nutsuwa', watau wanda ya nutsu da imani da kyawawan ayyuka. Sai a umarce shi da ya koma zuwa ga Ubangijinsa yana mai yarda da sakamakon da za a ba shi, yana kuma yardajje a wurin Ubangijinsa saboda imaninsa da kyawawan ayyukansa. Sai kuma Allah ya umarce shi da ya shiga cikin ayarin bayinsa nagari, ya shiga Aljannar da Allah ya tanadar musu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman matsayin garin Makka a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Zaman Annabi (ﷺ) a cikin Makka yana daga cikin dalilan ɗaukakar darajarta.

3. Halatta wa Annabi (ﷺ) garin Makka wani albishir ne a gare shi na samun nasara a kan maƙiyansa mushirikan Makka, domin wannan Sura *Makkiyya* ce, kuma abin da aka ambata a nan bai tabbata ba sai bayan ya yi hijira zuwa Madina da wasu shekaru.

4. Tabbatar da mu'ujizar Alƙur'ani ta ba da labarin gaibu kafin ya tabbata.

5. Rantsuwa da mahaifi da abin da ya haifa tana nuni zuwa ga girman hikimar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) wajen samar da halittunsa ta hanyar hayayyafa, da kuma wahalhalun da mahaifa suke sha wajen tarbiyya, don ganin abin da aka haifa ya kai ga cikar ƙarfinsa da Allah ya ƙaddara masa.

6. Rayuwar ɗan'adam cike take da wahalhalu da rashin hutu, tun sanda zai zo duniya har zuwa lokacin komawarsa ga Mahaliccinsa. Don haka da ɗan'adam zai fahimci haka to da ya yi ƙoƙari ya kyautata aikinsa tun a nan duniya, don ya sami hutu na har abada a lahira.

90-Suratul Balad

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
An fi sanin wannan Sura da '*Suratul Balad*', watau da kalmar da ta zo a ayar farko a cikinta. A kuma cikin *Sahihul Bukhari* an kira ta da '*Suratu La Uƙsimu*'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin ɗaukacin malamai.

3. Jerin Saukarta:

Ita ce Sura ta talatin da biyar (35) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratu Kaf*' kafin '*Suratuḍ Ḍariḳ*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin ne (20).

5. Babban Jigonta:
Bayanin cewa ɗan'adam yana cikin wahala a duniya da lahira matuƙar bai yi imani ya yi aiki nagari ba.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Bayanin matsayin garin Makka a wurin Allah.
• Darajar da garin Makka ya samu saboda zaman Manzon Allah (ﷺ) a cikinsa da kakanninsa annabawa, watau Annabi Ibrahim da ɗansa Annabi Isama'ila.
• Sukan mushirikai masu ƙaryata tashin alƙiyama da kuma yawan alfahari da haka da rashin gode wa ni'imar Allah a gare su.
• Narko ga kafirai da albishir ga muminai.

Suratul Balad (1-4)

لَآ أُقۡسِمُ بِهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ۝١ وَأَنتَ حِلُّۢ بِهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ۝٢ وَوَالِدٖ وَمَا وَلَدَ ۝٣ لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِي كَبَدٍ ۝٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da wannan gari (na Makka).

2. Alhali kuwa kai an halatta maka wannan gari.

3. (Na rantse) da mahaifi da abin da ya haifa.

4. Haƙiƙa Mun halicci mutum cikin wahala.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da garin Makka, musamman lokacin da Manzon Allah (ﷺ) yake zaune a cikinsa. Ko kuma yana nufin, alhalin Manzon Allah (ﷺ) an halatta masa abin da zai aikata a cikin garin Makka na kashe duk wanda ya cancanci kisa. Wannan tafsirin shi ne aka ruwaito daga magabata, kamar Abdullahi ɗan Abbas da almajiransa. Ya kuma rantse da mahaifi, watau Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ko kuma duk wani mahaifi. Ya rantse da abin da mahaifi ya haifa, watau zurriyar Annabi Adamu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ko kuma duk wani wanda aka haifa.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wannan rantsuwa ne don ya tabbatar da cewa, lalle ya halicci ɗan'adam cikin wahala, saboda abin da yake fuskanta na wahalhalun duniya da masifunta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɗagawar ɗan'adam da girman kansa idan ya ga ya samu wadata.

2. Duk wanda yake kashe dukiyarsa wajen biyan buƙatunsa na sha'awa cikin saɓon Allah, to wannan yana hallakar da dukiyarsa ne a inda ba zai amfana da komai ba sai dai asara da nadama.

3. Duk abin da bawa yake aikatawa, to ya riƙa tuna cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ganin sa, kuma mala'ikunsa suna rubuta komai; ƙarami da babba kuma zai gamu da sakamakonsa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan'adam ɗimbin ni'imomi waɗanda dukiyarsa da ƙarfinsa ba za su samar masa su ba, don haka wajibi ne ya riƙa tuna su yana tsayawa da haƙƙoƙin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da suke a kansa, yana gode masa, yana kuma amfani da waɗannan ni'imomi wajen biyayya ga Allah ba wajen saɓa masa ba.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa ɗan'adam hanyoyin alheri da na sharri, watau na shiriya da na ɓata, ya rage ga mutum ya zaɓi ɗaya daga cikinsu, amma dai ya sani cewa, akwai sakamako a cikin kowacce ya zaɓa, don haka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba mai zaluntar kowa ba ne.

Suratul Balad (5-10)

أَيَحۡسَبُ أَن لَّن يَقۡدِرَ عَلَيۡهِ أَحَدٞ ۝٥ يَقُولُ أَهۡلَكۡتُ مَالٗا لُّبَدًا ۝٦ أَيَحۡسَبُ أَن لَّمۡ يَرَهُۥٓ أَحَدٌ ۝٧ أَلَمۡ نَجۡعَل لَّهُۥ عَيۡنَيۡنِ ۝٨ وَلِسَانٗا وَشَفَتَيۡنِ ۝٩ وَهَدَيۡنَٰهُ ٱلنَّجۡدَيۡنِ ۝١٠

5. Yanzu mutum yana tsammanin cewa wani ba zai sami iko a kansa ba?

6. Yana cewa: "Na ɓatar da dukiya mai ɗimbin yawa."

7. Shin yana tsammanin cewa ba wanda ya gan shi?

8. Shin ba Mu sanya masa idanuwa biyu ba ne?

9. Da harshe da kuma laɓɓa biyu?

10. Muka kuma bayyana masa hanyoyi biyu?

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalin ɗan'adam game da girman kai da yake yi yana saɓon Allah, ya nuna masa cewa, yanzu yana tsammani ne cewa, wani ba zai sami iko a kansa ba idan ya aikata laifuka, don haka ya fi ƙarfin a kama shi da laifinsa ko da kuwa Ubangijinsa ne mahaliccinsa? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ɗan'adam yana gadara da cewa, ya kashe maɗuɗuwar dukiya mai yawan gaske. Shin tsammani yake cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya ganin sa, kuma ba zai yi masa hisabi a kan wannan dukiyar tasa ba; ta ina ya same ta, kuma ta ƙaƙa ya kashe ta? Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tunatar da shi ni'imomin da ya yi masa waɗanda ba zai iya sayen su da kuɗi ba. Ya tabbatar masa cewa, shi ne ya sanya masa idanuwa biyu da yake gani da su. Ya kuma yi masa harshe da laɓɓa biyu waɗanda da su ne yake iya magana. Ya kuma nuna masa hanyoyi biyu; hanyar alheri da hanyar sharri. Duk waɗannan ni'imomi ne da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan'adam amma sai yake butulce masa, ya ƙi gode masa ta hanyar yi masa biyayya.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wanda duk zai bi hanyar alheri to sai ya kauce wa son zuciya da sha'awace-sha'awace, ya rungumi ayyukan jin ƙai don Allah.

2. ‘Yanta bayi da ciyar da mabuƙata a lokacin tsanani da yin imani da Allah da yi wa juna wasiyya da haƙuri da tausayi, suna daga cikin abubuwan da suke kai bawa shiga Aljanna.

3. Jan hankalin masu wadata a kan cewa, maimakon su kashe dukiyarsu wajen ɓarna da saɓon Allah, kamata ya yi su kashe ta wajen taimakon mabuƙata, domin a nan ne za su sami lada, kuma da shi ne za su yi alfahari.

4. Duk da cewa shari’a ta ƙuntata hanyoyin bautar da ɗan’adam sai kuma ta yawaita hanyoyin samar wa da bayi ‘yanci, ta sanya aikata haka yana daga cikin hanyoyin samun lada ko yin kaffara.

5. Bayyana cewa mushirikai babu abin da suka iya sai tinƙaho da alfahari da tarin dukiya da neman suna, amma ba su damu da taimakon masu rauni ba, domin wannan abu ne da Musulunci ne ya zo da shi, ya kuma kwaɗaitar da ‘ya’yansa a kan aikata shi.

6. **Ɓ**arnar dukiya a wuraren bukukuwa ko walima ba shi ne abin da zai amfani mabuƙata ba, domin sau tari ba su ake gayyata irin waɗannan wurare ba, sai dai a gayyaci waɗanda ba su da buƙatar wannan abincin.

Suratul Balad (11-20)

فَلَا ٱقْتَحَمَ ٱلْعَقَبَةَ ﴿١١﴾ وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا ٱلْعَقَبَةُ ﴿١٢﴾ فَكُّ رَقَبَةٍ ﴿١٣﴾ أَوْ إِطْعَٰمٌ فِى يَوْمٍ ذِى مَسْغَبَةٍ ﴿١٤﴾ يَتِيمًا ذَا مَقْرَبَةٍ ﴿١٥﴾ أَوْ مِسْكِينًا ذَا مَتْرَبَةٍ ﴿١٦﴾ ثُمَّ كَانَ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَتَوَاصَوْا۟ بِٱلصَّبْرِ وَتَوَاصَوْا۟ بِٱلْمَرْحَمَةِ ﴿١٧﴾ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْمَيْمَنَةِ ﴿١٨﴾ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا هُمْ أَصْحَٰبُ ٱلْمَشْـَٔمَةِ ﴿١٩﴾ عَلَيْهِمْ نَارٌ مُّؤْصَدَةٌ ﴿٢٠﴾

11. Sai bai ƙetare hanya mai wahala ba?.

12. Me kuma ya sanar da kai mece ce hanya mai wahala?

13. (Watau) ‘yanta wuyaye (bawa ko baiwa).

14. Ko kuma ciyarwa a wata rana ta yunwa.

15. Ga maraya ma'abocin kusanci.

16. Ko miskini ma'abocin talauci.

17. Sannan kuma ya zama daga waɗanda suka yi imani, suka yi wa junansu wasiyya da yin haƙuri kuma suka yi wa juna wasiyya da tausayawa.

18. Waɗannan su ne ma’abota dama.

19. Waɗanda kuwa suka kafirce wa ayoyinmu, su ne ma’abota hagu.

20. A kansu akwai wuta abar kullewa.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wa ɗan’adam cewa, ana buƙatar sa da ya

ƙetare hanya mai wahala wadda ta raba tsakaninsa da gidan Aljanna, domin ya samu damar bin hanyar alheri, to amma sai bai ƙetare ta ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanar da Manzonsa (ﷺ) wannan mawuyaciyar hanya da cewa su ne:
Na ɗaya, ‘yanta bawa ko baiwa domin Allah.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda), ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk wanda ya ‘yanta baiwa ko bawa mumini, to a madadin kowace gaɓa ɗaya ta wannan bawan Allah zai ‘yanta masa gaɓarsa daga shiga wuta.” [Bukhari #2517 da Muslim #1509].

Na biyu, ciyar da marayan da ya rasa ubansa sannan kuma yana da dangantaka ta zumunci da shi. Ko kuma ciyar da mabuƙaci wanda bai mallaki abin da zai ishe shi ba. Ya ciyar da su a lokacin da ake fama da yunwa saboda ƙarancin abinci.

An karɓo daga Salmanu ɗan Amir (Allah ya ƙara masa yarda), ya ce: Na ji Manzon Allah (ﷺ) yana cewa: “Sadaka ga mabuƙaci sadaka ce kawai, amma ga makusanci abu biyu ne; sadaka ce, kuma sada zumunci ne.” [Ahmad #16227 da Tirmizi #658 da Nasa’i #2582].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, bayan waɗannan kyawawan ayyukan kuma ya kasance daga cikin waɗanda suka yi imani, suka kuma yi wa junansu wasiyya da yin haƙuri a kan bin Allah da kauce wa saɓa masa da kuma yin haƙuri a kan abin da zai same su na ƙaddara marar daɗi, suka kuma yi wa juna wasiyya da tausaya wa bayin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda), ya ce: “Masu tausayi, Allah mai rahama yana tausaya musu. Ku tausaya wa mutane a ƙasa sai Allah a sama ya tausaya muku ku ma.” [Abu Dawud #4941 da Tirmizi #1924 da Ahmad #6494].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, masu irin waɗannan siffofi su ne ma’abota dama, domin sun biya haƙƙin Allah da haƙƙoƙin bayinsa, sun kuma guji abin da ya hana.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, waɗanda suka kafirce wa ayoyinsa da ya saukar wa Manzonsa (ﷺ), to waɗannan su ne ma’abota hagu, za su kuma shiga wutar Jahannama a ranar alƙiyama inda za a kulle su a cikinta, a yi ta yi musu azaba babu ranar fita daga cikinta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana iya yin rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga halittunsa. Amma bawa ba zai iya rantsuwa ba sai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Tsarkake zuciya da kyawawan ayyuka hanya ce ta samun rabauta a gidan Aljanna.

3. Nuni zuwa ga cewa hasken wata daga hasken rana yake, shi ba ya da haskensa na kansa.

4. Duk wani ɗan’adam Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kimsa masa gane gaskiya da ƙarya tun farkon halittarsa, sai dai daga baya ne wasu abubuwa suke gurɓata shi.

91-Suratus Shams

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da *'Suratus Shams'*, watau an kira ta da kalmar da ta zo a ayarta ta farko. A cikin littafin *Sahihul Bukhari* an kira ta da '*Suratu Was-Shamsi Wa Dhuhaha*', watau da ambaton ayarta ta farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu wani saɓani.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ashirin da shida (26) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Kadr'* gabanin *'Suratul Buruj'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha biyar ne (15) a lissafin yawancin malamai. Amma a lissafin mutanen Makka adadinsu goma sha shida ne (16).

5. Babban Jigonta:
Surar tana Jan hankali ne zuwa ga tsarkake zuciya da guje wa saɓon Allah domin kauce wa hushinsa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Jawo hankula game da wasu manyan ayoyi masu nuna girman Kudurar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da cancantar a bauta masa shi kaɗai.
• Tsoratar da mushirikai cewa, su guje wa abin da zai jawo musu azabar Allah, watau ƙaryata Manzonsa (ﷺ), kamar yadda ya faru ga wasu al'ummu da suka gabace su.

Suratus Shams (1-10)

وَٱلشَّمۡسِ وَضُحَىٰهَا ۝١ وَٱلۡقَمَرِ إِذَا تَلَىٰهَا ۝٢ وَٱلنَّهَارِ إِذَا جَلَّىٰهَا ۝٣ وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰهَا ۝٤ وَٱلسَّمَآءِ وَمَا بَنَىٰهَا ۝٥ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا طَحَىٰهَا ۝٦ وَنَفۡسٖ وَمَا سَوَّىٰهَا ۝٧ فَأَلۡهَمَهَا فُجُورَهَا وَتَقۡوَىٰهَا ۝٨ قَدۡ أَفۡلَحَ مَن زَكَّىٰهَا ۝٩ وَقَدۡ خَابَ مَن دَسَّىٰهَا ۝١٠

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da rana da walaharta.

2. Da kuma wata idan ya bi ta (wato ranar).

3. Da kuma wuni idan ya bayyana ta.

4. Da kuma dare idan ya lulluɓe ta.

5. Da kuma sama da gininta.

6. Da kuma ƙasa da shimfiɗarta.

7. Da kuma rai da daidaitarsa.

8. Sai Ya kimsa masa (gane) lalacewarsa da taƙawarsa.

9. Haƙiƙa wanda ya tsarkake shi (ran) ya rabauta.

10. Haƙiƙa kuma wanda ya binne shi da saɓo ya taɓe.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da rantsuwa har goma sha ɗaya don nuna muhimmancin abin da zai zo da bayaninsa a cikinta.

Na ɗaya, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi rantsuwa da rana, domin ita wata babbar halittar Allah ce mai nuna cikar Kudurar wanda ya samar da ita.

Na biyu, ya yi rantsuwa da lokacin hasken walaharta, watau lokacin rana da ta fara haske bayan ta hudo daga mahudarta.

Na uku, ya yi rantsuwa da wata idan ya biyo bayan faɗuwar rana.

Na huɗu, ya yi rantsuwa da wuni idan ya bayyana abin da yake kan ƙasa da haskensa.

Na biyar, ya rantse da dare idan ya lulluɓe ƙasa da duhunsa.

Na shida, ya rantse da sama da ya ɗaga ta ba tare da wasu dirkoki ba.

Na bakwai, ya rantse da ginin sama wanda ya kyautata halittarsa, ya daidaita shi.

Na takwas, ya yi rantsuwa da ƙasa wadda ya halicce ta, domin rayuwar ɗan'adam a kanta.

Na tara, ya rantse da shimfiɗar ƙasa da daidaita ta, don ɗan'adam ya ji daɗin zama da tafiya a kanta.

Na goma, ya yi rantsuwa da kowane rai da ya halitta.

Na sha ɗaya, ya rantse da yadda ya daidaita halittar kowane rai, sannan ya kimsa masa sanin abu mai kyau, don ya aikata shi da sanin mummuna don ya guje shi.

Sai kuma ya bayyana sakamakon wanda ya tsarkake ransa da kyawawan ayyuka da ɗabi'u da cewa ya rabauta, ya sami abin da yake so, sannan wanda ya binne shi da saɓon Allah da laifuka da miyagun ɗabi'u shi kuma ya taɓe ya yi asara.

An karɓo daga Imrana ɗan Husain (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wasu mutane biyu daga ƙabilar Muzaina sun zo wurin Manzon Allah (ﷺ) suka ce: Ya Manzon Allah, ka ba mu labari game da abin da mutane suke aikatawa a yau (watau duniya), suke wahala a kansa, shin wani abu ne na ƙaddara da aka riga aka hukunta musu aka kuma zartar musu da shi, ko kuma wani sabon abu ne wanda suke fuskanta daga abin da Annabinsu ya zo musu da shi, hujja kuma ta tabbata a kansu? Sai ya ce: "A'a, abu ne da aka riga aka hukunta musu aka kuma zartar musu da shi. Abin da yake gaskata wannan a littafin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne faɗar Allah: *'Da kuma rai da daidaitarsa. Sai ya kimsa masa (gane) lalacewarsa da taƙawarsa*'...." [Muslim #2650 da Ahmad #19936].

An karɓo daga Zaidu ɗan Arƙam (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance yana cewa: "Ya Allah, lalle ni ina neman tsarinka daga gazawa da kasala da ragwanci da rowa da tsufa tukub da azabar ƙabari. Ya Allah, ka ba wa raina taƙawarsa, ka tsarkake shi, kai ne fiyayyen mai tsarkake shi, kai ne majiɓincin sa mai taimakon sa...." [Muslim #2722 da Nasa'i #5458].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Ɗagawa da girman kai sukan zama sanadiyyar bijire wa gaskiya da rungumar ƙarya.

2. Duk waɗanda suka goyi bayan laifi, ko suka taimaka wajen yin sa, daidai suke da masu laifin.

3. Zunubai su ne suke jawo uƙubar duniya kafin ta lahira.

Suratus Shams (11-15)

كَذَّبَتْ ثَمُودُ بِطَغْوَىٰهَآ ﴿١١﴾ إِذِ ٱنۢبَعَثَ أَشْقَىٰهَا ﴿١٢﴾ فَقَالَ لَهُمْ رَسُولُ ٱللَّهِ نَاقَةَ ٱللَّهِ وَسُقْيَىٰهَا ﴿١٣﴾ فَكَذَّبُوهُ فَعَقَرُوهَا فَدَمْدَمَ عَلَيْهِمْ رَبُّهُم بِذَنۢبِهِمْ فَسَوَّىٰهَا ﴿١٤﴾ وَلَا يَخَافُ عُقْبَىٰهَا ﴿١٥﴾

11. Samudawa sun ƙaryata saboda ɗagawarsu.

12. Yayin da mafi tsagerancinsu ya zabura.

13. Sai Manzon Allah ya ce da su: “Ku bar taguwar Allah da (ranar) shanta.”

14. Sai suka ƙaryata shi sannan suka soke ta, sai Ubangijinsu Ya kama su da azaba saboda zunubinsu, sai Ya daidaita ta (watau ƙabilar wajen azaba).

15. Kuma ba Ya tsoron abin da zai biyo bayanta.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana yi wa mushirikan Kuraishawa masu ƙaryata Manzon Allah (ﷺ) kashedi da cewa, Samudawa sun ƙaryata Annabinsu Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) saboda ƙetare iyakarsu da saɓon Allah da miyagun laifuka, lokacin da mafi tsagerancinsu ya zabura ya nufi taguwar Allah da niyyar zai soke ta, yayin da mutanensa suka zuga shi a kan haka. Sai Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya gargaɗe su, ya ja musu kunne a kan su ƙyale taguwar Allah da ranar shan ruwanta, kada su yi ƙoƙarin cutar da ita. To amma sai suka ƙaryata Manzonsu Annabi Salihu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), suka yi watsi da nasiharsa dangane da wannan taguwar, sai tsageran cikinsu ya kashe ta, duk sauran kuma suka goyi bayansa, sai suka zama abokan tarayyarsa a wajen laifi. A kan haka ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar musu da azabarsa wadda ta mamaye su gaba ɗaya, ya hallaka su da tsawa saboda mummunan laifinsu, ya kuma daidaita su a wajen uƙuba bai bambance wani daga cikinsu ba.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yi musu wannan azabar, ya hallaka su gaba ɗaya, ba tare da yana jin tsoron abin da zai biyo bayanta ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Halittar abubuwa masu kishiyantar juna, kamar dare da wuni da namiji da mace, wani babban dalili ne mai tabbatar da girman Kudurar Allah mahaliccin kowa da komai.

2. Akwai ƙwaƙƙwarar alaƙa tsakanin rantsuwar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi da dalilin yin rantsuwar, watau ayyukan mutane akwai na alheri akwai kuma na sharri, kamar yadda a lokaci ake da haske da duhu. Hakanan ayyukan mutane sukan haifar da abu mai amfani da marar amfani, kamar yadda namiji da mace sukan haifi zurriya ta ƙwarai da wadda ba ta ƙwarai ba.

3. Rantsuwa da dare da wuni jan hankali ne zuwa ga hikimomin Allah da suke cikinsu, kamar yadda suke ɗauke da ishara zuwa ga ɓata da shiriya.

4. Rantsuwa da halittar mace da namiji tana nuna cikar Kudurar Allah da girman hikimarsa ta yin halittar komai jinsi biyu, namiji da mace domin yaɗa dangin kowace halitta da wanzar da ita.

5. Bambancin ayyukan mutane saboda bambancin manufofin masu ayyukan da gwargwadon sakamakon kowane aiki. Wanda ya yi aikinsa don Allah da neman yardarsa, to wannan shi ne aikinsa zai amfane shi. Wanda kuwa ya yi aikinsa ba don Allah ba wannan shi ne wanda zai yi asarar aikinsa, kuma ya gamu da mummunan sakamako.

92-Suratul Lail

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura a yawancin *masahifu* da wasu littattafan tafsirai an kira ta da '*Suratul Laili'*. Amma a wasu littattafan tafsirai an kira ta da '*Suratu Wal-Laili'*. A cikin littafin Bukhari da Tirmizi kuwa sun kira ta '*Suratu Wal-Laili Iza Yaghsha'*.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin yawancin malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tara (9) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *'Suratul A'ala'* kafin *'Suratul Fajri'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta ashirin da ɗaya ne (21).

5. Babban Jigonta:
Surar tana bayanin bambance-bambancen mutane saboda bambancin manufofinsu da kuma sakamakon ayyukan kowanne daga cikinsu.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Bayanin martabar muminai da kyawawan ayyukansu da ƙasƙancin mushirikai da munanan ayyukansu.
• Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana shiryar da wasu bayinsa zuwa ga alheri yana kuma yi musu kyakkyawan sakamako, kamar yadda yake ɓatar da wasu ya yi musu mummunan sakamako.
• Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko Manzonsa (ﷺ) don tunatarwa da gargaɗi, wasu sun ji tsoron Allah sun bi shi, sun amfana a rayuwar duniya da ta lahira. Wasu kuma sun bijire masa saboda son duniya; su kam za su gamu da sakamakon wuta mafi girma.

Suratul Lail (1-4)

وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰ ۝١ وَٱلنَّهَارِ إِذَا تَجَلَّىٰ ۝٢ وَمَا خَلَقَ ٱلذَّكَرَ وَٱلۡأُنثَىٰٓ ۝٣ إِنَّ سَعۡيَكُمۡ لَشَتَّىٰ ۝٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da dare idan ya lulluɓe (da duhunsa).

2. Da kuma wuni idan ya bayyana.

3. Da kuma halittar namiji da mace.
4. Lalle aikinku ya sha bamban.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa iri uku:
Ta ɗaya, ya rantse da dare yayin da ya lulluɓe komai da duhunsa, kowa ya koma mazauninsa don ya huta daga kujuba-kujuba da ɗawainiyar rana.
Ta biyu, ya rantse da wuni idan ya bayyana da haskensa, mutane da dabbobi da tsuntsaye suka fita don neman abincinsu.
Ta uku, ya rantse da halittar komai jinsi biyu; namiji da mace, don nuna cikakkiyar Ƙudurarsa da hikimarsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da bambancin ayyukan bayinsa, daga cikinsu akwai kyawawan ayyuka waɗanda su ne sanadiyyar shigar bawa Aljanna; akwai kuma munanan ayyuka waɗanda su ne sanadiyyar shigarsa wuta.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Bayar da haƙƙoƙin Allah da kiyaye dokokinsa da gaskata alƙawarinsa su ne sanadiyyar samun sauƙi ga bawa cikin dukkan al'amuransa.

2. Rowa da hana haƙƙoƙin Allah da ƙaryata alƙawarinsa, su ne sanadiyya shigar bawa cikin dukkan tsanani da wahala.

3. Duk wanda ya nufi aikin alheri Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana hore masa hanyoyinsa, wanda kuma ya nufi mummunan aiki shi ma Allah yana hore masa hanyoyinsa, domin ya kama shi da hujja.

4. Aiki nagari yana haifar da wani aikin nagari irinsa. Hakanan mummunan aiki yana haifar da wani mummunan aiki irinsa.

Suratul Lail (5-11)
فَأَمَّا مَنْ أَعْطَىٰ وَٱتَّقَىٰ ۝٥ وَصَدَّقَ بِٱلْحُسْنَىٰ ۝٦ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلْيُسْرَىٰ ۝٧ وَأَمَّا مَنۢ بَخِلَ وَٱسْتَغْنَىٰ ۝٨ وَكَذَّبَ بِٱلْحُسْنَىٰ ۝٩ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلْعُسْرَىٰ ۝١٠
وَمَا يُغْنِى عَنْهُ مَالُهُۥٓ إِذَا تَرَدَّىٰٓ ۝١١

5. To wanda ya ba da (haƙƙoƙin da ke kansa) ya kuma yi taƙawa.

6. Ya kuma gaskata (sakamako) mafi kyau.

7. To lalle ne za Mu sauƙaƙa masa (hanyar) Aljanna.

8. Amma kuma wanda ya yi rowa (da haƙƙin Allah) ya kuma wadatu (da neman lada).

9. Kuma ya ƙaryata (sakamako) mafi kyau.

10. To lalle ne za Mu hore masa (hanyar) wuta.

11. Dukiyarsa kuma ba za ta amfane shi ba idan ya gangara (cikin wuta).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana bambancin ayyukan bayinsa da sakamakon kowane mai aiki, da cewa, duk wanda ya bayar da haƙƙoƙin da suke kansa, ya kuma guji abin da aka hana shi na saɓon Allah, ya kuma gaskata alƙawarin da Allah ya yi masa na ba shi madadin abin da ya ciyar domin shi, ya kuma gaskata alƙawarin gidan Aljanna da aka yi wa mai ciyar da dukiyarsa don Allah, to wannan lalle Allah zai sauƙaƙe masa ayyukan alheri da ciyarwa don Allah, domin ya kai shi ga samun gidan Aljanna.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, duk wanda ya yi rowa da dukiyarsa, bai fitar da haƙƙoƙin da ke cikinta ba, ya ƙanƙame dukiyarsa ya saki Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya neman falalarsa, ya kuma ƙaryata alƙawarin Allah na bayar da madadi ga wanda ya ciyar da dukiyarsa dominsa, da sakamakon Aljanna ga mai bayarwa don Allah, to wannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai hore masa munanan ayyuka, ya tsaurara masa ya hana shi aikata alheri. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, dukiyarsa da yake rowar ta, ya ƙi aikin alheri da ita ba za ta amfana masa komai ba lokacin da ya faɗa cikin hallaka aka jefa shi cikin wutar Jahannama.

An karɓo daga Aliyyu ɗan Abu Ɗalibi (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Mun kasance a wurin wata jana’iza a maƙabartar 'Baƙi’ul Gharƙadi', sai Manzon Allah (ﷺ) ya zo mana, ya sami wuri ya zauna, mu ma muka zauna kewaye da shi, yana riƙe da kwagirinsa, sai ya sunkuyar da kansa ya riƙa tona ƙasa da kwagirinsa, sannan ya ce: “Babu wani mutum ɗaya mai rai daga cikinku face an rubuta masa mazauninsa a Aljanna da wuta, sai kuma an rubuta ɗan wuta ne shi ko ɗan Aljanna.” Sai wani mutum ya ce: “Ya

Manzon Allah, yanzu ba ma dogara da abin da aka riga aka rubuta mana ba mu bar aiki? Wanda cikinmu ya zamanto ɗan Aljanna ne, to zai kama aikin ‘yan Aljanna; wanda yake ɗan wuta ne zai kama aikin ‘yan wuta?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Lalle ‘yan Aljanna za a sauƙaƙe musu aikata aikin ‘yan Aljanna, hakanan ‘yan wuta ma za a sauƙaƙe musu aikata aikin ‘yan wuta.” Sannan ya karanta faɗar Allah: “*To amma wanda ya ba da (hakkokin da ke kansa) ya yi takawa...*...” har zuwa ƙarshen ayoyi.” [Bukhari #1362 da Muslim #2647].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yanke uzuri ga bayinsa, ya aiko musu da Manzo ya kuma saukar musu littafi, ya yi musu bayanin shiriya da ɓata, don haka duk wanda ya ga dama ya zaɓi shiriya ko ya zaɓi ɓata, zai ga sakamakon zaɓinsa a ranar alƙiyama.

2. Duniya da lahira na Allah ne, shi ne ya tsara komai a cikinsu bisa zaɓinsa da ganin damarsa, duk abin da ya yi wa bawa baiwa da shi na shiriya a duniya da kyakkyawan sakamako a lahira, wannan falalarsa ce babu mai tilasta masa.

3. Falalar Sayyidina Abubakar (Allah ya kara masa yarda) da yabon da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa tare da tsarkake niyyarsa da yi masa alƙawarin sakamako mai girma a ranar alƙiyama wanda zuciyarsa za ta gamsu da shi.

Suratul Lail (12-21)

إِنَّ عَلَيۡنَا لَلۡهُدَىٰ ١٢ وَإِنَّ لَنَا لَلۡأٓخِرَةَ وَٱلۡأُولَىٰ ١٣ فَأَنذَرۡتُكُمۡ نَارٗا تَلَظَّىٰ ١٤ لَا يَصۡلَىٰهَآ إِلَّا ٱلۡأَشۡقَى ١٥ ٱلَّذِي كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ١٦ وَسَيُجَنَّبُهَا ٱلۡأَتۡقَى ١٧ ٱلَّذِي يُؤۡتِي مَالَهُۥ يَتَزَكَّىٰ ١٨ وَمَا لِأَحَدٍ عِندَهُۥ مِن نِّعۡمَةٖ تُجۡزَىٰٓ ١٩ إِلَّا ٱبۡتِغَآءَ وَجۡهِ رَبِّهِ ٱلۡأَعۡلَىٰ ٢٠ وَلَسَوۡفَ يَرۡضَىٰ ٢١

12. Lalle bayyana hanyar shiriya a kanmu yake.

13. Kuma lalle lahira da duniya namu ne.

14. Don haka ina yi muku gargaɗin wata wuta mai ruruwa.

15. Ba mai shigar ta sai mafi tsiyacewa.

16. Wanda ya ƙaryata ya kuma ba da baya.

17. Kuma lalle za a nesantar da mafi taƙawa daga gare ta.

18. Wanda yake ba da dukiyarsa yana neman tsarkaka.

19. Ba kuwa wani da ya yi masa wata ni'ima da za a saka masa (a kanta)

20. Sai dai don neman Fuskar Ubangijinsa Maɗaukaki.

21. Kuma lalle zai yarda (da sakamakon da za a ba shi).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ya yanke wa kowa hanzari, domin kuwa ya wajabta wa kansa bayanin hanyar shiriya da ta ɓata da abin da yake biyayya ne gare shi da wanda yake saɓo ne. Ya kuma tabbatar da cewa, rayuwar lahira da ta duniya duk nasa ne; shi ne yake yin abin da ya ga dama a cikinsu babu mai tilasta masa ko ya hana shi.
Sai kuma Allah ya gargaɗi bayinsa da azabar wuta mai tsananin ruruwa idan suka saɓa masa. Kuma babu wanda zai shiga wannan wutar ya ɗanɗani tsananin zafinta sai mafi tsiyacewa, watau kafiri, wanda ya ƙaryata Ubangijinsa da saƙon da ya aiko Manzonsa da shi, ya kuma juya baya, ya bijire wa bin Allah da Manzonsa.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wanda zai nesantar daga shiga wannan wuta, watau wanda yake mai matuƙar kiyaye dokokinsa. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta shi da cewa, shi ne wanda yake ciyar da dukiyarsa a ayyukan alheri, domin ya tsarkake kansa daga zunubai. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa shaida da cewa, ba yana ciyar da dukiyarsa ne don ya saka wa wani a kan wata niʾima da ya yi masa ba. Ba ya nufin komai da ba da dukiyarsa sai don neman fuskar Ubangijinsa Maɗaukaki, kuma da sannu zai yarda da sakamakon da Allah zai ba shi a lahira na gidan Aljanna.
Da dama daga cikin malaman tafsiri sun bayyana cewa, waɗannan ayoyi sun sauka ne a kan Abubakar As-Siddiƙ (Allah ya kara masa yarda), wasu ma sun ce ijmaʾin malamai ne a kan haka. Haƙiƙa babu wanda ya fi cancanta da wannan ayar kamar Sayyidina Abubakar (Allah ya kara masa yarda), domin shi ne kan gaba a cikin wannan alʾumma wajen siffantuwa da waɗannan siffofi da aka ambata a waɗannan ayoyi, domin shi mutum ne mai yawan gaskiya da tsoron Allah da bin dokokinsa sau-da-ƙafa da ciyar da dukiyarsa, don taimakon addinin Allah da Manzon Allah (ﷺ). Ya bayar da ilahirin dukiyarsa domin Allah da neman yardarsa, ba wai don yana biyan wani mutum wani alheri da ya taɓa yi masa ba, bai kuma taɓa neman wani ya yi masa sakayya a kan haka in ba Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba. Don haka shi ya fi kowa cancantar wannan falala.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya kara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Duk wanda ya ciyar da dangogi biyu na dukiyarsa (watau kamar dirhami biyu ko dinari biyu) don Allah, za a kira shi ta ƙofofin Aljanna da cewa: Ya bawan Allah, (taho) ga alheri. Duk wanda ya kasance cikin maʾabota salla, to za a kira shi ta ƙofar salla; wanda kuma ya zamanto daga maʾabota jihadi, za a kira shi ta ƙofar jihadi; wanda ya kasance cikin maʾabota azumi, to za a kira shi ta ƙofar Rayyan; wanda ya kasance cikin maʾabota sadaka, to za a kira shi ta ƙofar sadaka.” Sai Abubakar (Allah ya kara masa yarda) ya ce: “Ya Manzon Allah, mahaifina da mahaifiyata fansa ne a gare ka, babu wata cutuwa tare da duk wanda za a kira shi ta waɗannan ƙofofi, to shin akwai wanda za a kira shi ta ƙofofin nan gaba ɗayansu?” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Naʾam, ina fatan kana cikinsu.” [Bukhari #1897 da Muslim #1027].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rantsuwa da duk abin da ya ga dama daga cikin halittarsa domin jan hankali ga muhimmancinsa ko wata hikima tasa da ke cikinsa.

2. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya kula da Manzonsa (ﷺ) tun yana ƙarami har girmansa, ya yi masa tarbiyyar da babu wani mahluƙi da ya taɓa samun irinta. Kuma tun sanda ya so shi bai taɓa fushi da shi ba.

3. Kamar yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya fifita sakamakon Manzon Allah (ﷺ) na lahira a kan na duniya, hakanan a cikin duk wani yanayi na rayuwarsa yana ganin daɗuwar alheri ne da izza a kullum, domin koyaushe a gunsa yau ta fi jiya, gobe kuma ta fi yau, har zuwa lokacin da Allah ya gama ba shi nasara a kan maƙiyansa, ya cika masa addininsa da niʾimarsa.

93-Suratud Dhuha

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta fi shahara da *'Suratud Dhuha'*. Amma a cikin wasu littattafan tafsiri da Sahihul Bukhari an kira ta da '*Suratu Wad-Dhuha'*, watau an ambace ta da ayarta ta farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:

Sura ce *Makkiyya* babu wani saɓani.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma sha ɗaya (11) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Fajri*' kafin '*Suratul Inshirahi*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha ɗaya ne (11).

5. Dalilin Saukarta:
An karɓo daga Jundub ɗan Sufyan (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya yi rashin lafiya sai bai samu yin ƙiyamul laili ba na kwana biyu ko uku, sai wata mace (kafira) ta zo wurinsa ta ce: "Ya Muhammadu, ina fatan shaiɗaninka ya rabu da kai, don na ga kwana biyu ko uku bai kusance ka ba." Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da wannan Sura. [Bukhari #4950 da Muslim #1797].

6. Babban Jigonta:
Bayanin ni'imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) na kulawa da shi da wahayin da ya saukar masa don ƙara sa masa nutsuwa da kwantar masa da hankali.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Rushe da'awar wasu mushirikai ta cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi watsi da Manzonsa (ﷺ) ya daina yi masa wahayi.
• Yi masa albishir da cewa ladansa a lahira ya fi na duniya, domin kuwa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai yi ta ba shi har sai ya yarda.
• Tunatar da shi kulawar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi da shi tun yana yaro har zuwa girmansa, domin ya yi masa godiya a kan ni'imominsa.

Suratud Dhuha (1-5)
وَٱلضُّحَىٰ ۝١ وَٱلَّيۡلِ إِذَا سَجَىٰ ۝٢ مَا وَدَّعَكَ رَبُّكَ وَمَا قَلَىٰ ۝٣ وَلَلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ لَّكَ مِنَ ٱلۡأُولَىٰ ۝٤ وَلَسَوۡفَ يُعۡطِيكَ رَبُّكَ فَتَرۡضَىٰٓ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da lokacin hantsi.

2. Da kuma dare idan ya yi tsit.

3. Ubangijinka bai bar ka ba, kuma bai ƙi ka ba.

4. Kuma lalle lahira ta fi maka alheri a kan duniya.

5. Kuma lalle Ubangijinka zai ba ka har sai ka yarda (da abin da Ya ba ka).

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da lokacin hantsi, wanda shi ne farkon wuni. Ya kuma rantse da dare lokacin da yi tsit ya lulluɓe komai da duhunsa, mutane suka koma mazaunansu don su huta su yi barci.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin rantsuwarsa da cewa, bai ƙyale Annabinsa (ﷺ) ba bai kuma yi fushi da shi ba, kamar yadda mushirikai suke zargi, don ganin wahayi ya yanke masa na wani ɗan lokaci ƙanƙani.
Sai kuma ya yi masa albishir da cewa, tabbas lahira ta fi masa alheri a kan duniya, domin a can ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa tanadin ni'imomin da ba za su yanke ba.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Annabi (ﷺ) ya zo gidan 'yarsa Faɗima (Allah ya ƙara mata yarda) , sai bai shiga ba ya koma, da Aliyyu (Allah ya ƙara masa yarda) ya dawo sai ta gaya masa. Sai ya je ya tambayi Manzon Allah (ﷺ), sai ya ce masa: "Na ga labule ne mai zane a ƙofarta, ina ni ina duniya?" Sai Aliyyu ya dawo wajen Faɗima (Allah ya ƙara mata yarda) ya faɗa mata abin da ya ce. Sai ta ce: "Ya ba ni duk umarnin da ya ga dama in yi da shi." Sai ya ce: "Ta aika wa wane, domin gida ne da suke cikin buƙata." [Bukhari #2613].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kwanta ya yi barci a kan wata tabarma har alamunta suka bayyana a gefen jikinsa, sai muka ce: Ya Manzon Allah, da ka sami shimfiɗa mai laushi. Sai ya ce: "Ina ni ina duniya? Ni a duniya ba wani ba ne sai kamar mahayi ne da ya sauka ya sha inuwar wata bishiya sannan ya tashi ya bar ta." [Tirmizi #2377, da Al-Albani, *As-Sahiha* #439].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa, lalle zai ba shi gwaggwaɓan sakamako, watau shi da al'ummarsa, har sai ya yarda da abin da aka ba shi aka ba al'ummarsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matsayin Annabi (ﷺ) a wurin Allah babu wani matsayi da ya kai shi.

2. Tabbatar wa mushirikai cewa, lalle alƙawarin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) mai tabbata ne babu makawa, domin idan sun lura za su ga yadda ya ba shi kulawa ta musamman tun yana ƙarami, ya tsare shi daga duk wani abu mai cutarwa, ya kyautata tarbiyyarsa, ya tashi a garin Makka kowa yana yabon sa. Lalle wanda ya yi masa wannan gatan, tabbas zai cika masa alƙawarinsa na ba shi nasara a kan magabtansa da kyakkyawan sakamako a lahira.
3. Wajabcin taimakon raunana cikin al'umma da tausasa musu zance.

4. Wajabcin godiya ga Allah da zantar da ni'imarsa ga bawa, ba ta hanyar fariya ko girman kai ba.

Suratud Dhuha (6-11)
أَلَمْ يَجِدْكَ يَتِيمًا فَاوَىٰ ﴿٦﴾ وَوَجَدَكَ ضَآلًّا فَهَدَىٰ ﴿٧﴾ وَوَجَدَكَ عَآئِلًا فَأَغْنَىٰ ﴿٨﴾ فَأَمَّا ٱلْيَتِيمَ فَلَا تَقْهَرْ ﴿٩﴾ وَأَمَّا ٱلسَّآئِلَ فَلَا تَنْهَرْ ﴿١٠﴾ وَأَمَّا بِنِعْمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثْ ﴿١١﴾

6. Shin bai same ka maraya ba sai Ya haɗa ka (da mai kula da kai)?

7. Ya kuma same ka marashin shiriya Ya shiryar (da kai)?

8. Ya kuma same ka matalauci Ya wadata (ka)?

9. Don haka maraya fa kada ka yi masa fin ƙarfi.

10. Mai tamabya kuma kada ka daka masa tsawa.

11. Amma kuma game da ni'imar Ubangijinka sai ka ba da labari.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya lissafa wa Manzonsa (ﷺ) wasu ni'imomi da ya yi masa a rayuwarsa, da cewa, ya same shi maraya, domin mahaifinsa ya rasu tun yana ciki, mahaifiyarsa ma ta rasu yana ɗan shekara shida, amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tanadar masa matsuguni, ya haɗa shi da mai kula da shi, watau kakansa Abdulmuɗɗalib sannan bayansa baffansa Abu Ɗalib.
Ya kuma tabbatar masa cewa, ya same shi marashin shiriya, bai san wani littafi ko imani ba, sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba shi shiriya, ya karantar da shi abin da bai sani ba.
Ya kuma tabbatar masa cewa, ya same shi matalauci ba ya da komai, amma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wadatar da shi, ya ba shi ganimar yaƙi mai yawa, ya kuma ba shi wadatar zuciya bayan ta dukiya.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Yawan kadara ba shi ne wadata ba; wadata ita ce wadatar zuci." [Bukhari #6446 da Muslim #1051].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya musulunta aka ba shi cin yau da na gobe, Allah ya ba shi wadatar zuci game da abin da ya ba shi, to haƙiƙa ya rabauta." [Muslim #1054].

Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ja hankalinsa da cewa, kada ya nuna wa maraya fin ƙarfi, ya yi masa kyakkyawar mu'amala da nuna masa tausayi. Hakanan shi ma mai tambaya saboda buƙata, kada ya yi masa tsawa. Kuma ya riƙa gode wa Allah bisa ni'imomin da ya yi masa, ya kuma riƙa ba da labarinsu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya cire duk wani rabon Shaiɗan daga zuciyar Manzonsa (ﷺ) ya yalwata masa ƙirjinsa yana karɓar duk wata doka ta addini cikin daɗin rai da nutsuwar zuciya, ya sanya masa son kira zuwa ga Allah da siffantuwa da kyawawan halaye da farat-farat da jama'a.

2. Duk wani laifi na Annabi (ﷺ) Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yafe masa shi. Wannan ya ƙunshi abubuwan da ya aikata ta hanyar ijtihadi amma suka saɓa da yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake so a yi su, kamar abin da ya faru tsakaninsa da Abdullahi ɗan Ummu Maktum (Allah ya ƙara masa yarda) , da karɓar fansa a kan ribatattun yaƙin Badar da haramta wa kansa shan zuma ko kuyangarsa Mariya (Allah ya ƙara mata yarda) .

3. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya sanya kyakkyawan yabon Manzonsa (ﷺ) a kan harsunan mutane a koyaushe, ya ɗaga masa matsayinsa zuwa martabar da babu wani mahluƙi da ya taɓa samun irinta. Duk sanda aka ambaci Allah, to za a ambacin Manzonsa (ﷺ) tare da shi, kamar lokacin shiga Musulunci, ko lokacin kiran salla da iƙama da tahiya da huɗuba da sauransu. Soyayyarsa da girmansa a cikin zukatan al'ummarsa ta kai matsayin da babu wani wanda ya sami kwatankwacinta cikin halittun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

94-Suratus Sharh

Mabudin Sura:

1. Sunanta:
An kira ta da '*Suratus Sharh'* a cikin wasu littattafan tafsiri da wasu *masahifu*. Amma a yawancin littattafan tafsiri da littafin *Sahihul Bukhari* da *Jami'ut Tirmizi* an kira ta da '*Alam Nashrah'*. A wasu littattafan tafsirin kuwa an kira ta da '*Suratul Inshirahi'*.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu wani saɓani a kai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma sha biyu (12) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratud Dhuha'* kafin *'Suratul Asri'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta takwas ne (8).

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) ne ta yaye masa duk wata damuwa da baƙin ciki da tafiyar masa da duk wani ƙunci na rayuwa da ƙara ɗaukaka darajarsa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Kulawar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bai wa Manzonsa (ﷺ) da luɗufin da ya yi masa na yaye masa duk wata damuwa da ƙunci da sauƙaƙe masa duk wani matsanancin abu.
• Ɗaukaka darajar Manzon Allah (ﷺ) da yaɗa ambatonsa a ko'ina har alƙiyama ta tsaya.

Suratus Sharh (1-4)

أَلَمْ نَشْرَحْ لَكَ صَدْرَكَ ۝١ وَوَضَعْنَا عَنكَ وِزْرَكَ ۝٢ ٱلَّذِىٓ أَنقَضَ ظَهْرَكَ ۝٣ وَرَفَعْنَا لَكَ ذِكْرَكَ ۝٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Shin ba Mu yalwata maka ƙirjinka ba?

2. Muka kuma sauke maka nauye-nauyenka?

3. Wanda ya nauyayi bayanka?

4. Muka kuma ɗaukaka maka ambatonka?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tuna wa Manzon Allah wasu manyan ni'imomi da ya yi masa, da cewa, ya yalwata masa ƙirjinsa, ya hore masa son sauraron wahayin da yake yiwo masa, da kuma juriya game da gallazawar mutanensa gare shi.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mala'iku sun zo min, sai suka kama ni suka nufi Rijiyar Zamzam da ni, sai aka tsaga ƙirjina sannan aka wanke shi da ruwan Zamzam, sannan suka sauko da ni." [Muslim #260].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo wa Manzon Allah (ﷺ) ya same shi a cikin yara yana wasa, sai ya kama shi, ya kwantar da shi, ya tsaga ƙirjinsa ya fito da zuciyarsa, ya cire wani gudan jini daga jikinta, ya ce: "Wannan rabon Shaiɗan ne a jikinka." Sannan ya sanya shi a cikin tasa ta zinariya ya wanke shi da ruwan Zamzam, sannan ya liƙe shi, ya mayar da shi wurinsa. Sai yara suka tafi a guje wajen mai renon sa, suka faɗa mata cewa, an kashe Muhammadu. Bayan sun nufo inda yake sai suka gamu da shi launin fatar jikinsa ya canza." [Muslim #261].

Allah kuma ya tabbatar masa cewa, ya sauke masa duk wani laifinsa wanda ya yi masa nauyi, kamar yana ɗauke da shi a gadon bayansa zai karya masa shi. Watau dai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gafarta masa duk wasu laifuka na baya da suka wuce da na nan gaba idan da za su samu.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa cewa, ya ɗaukaka ambatonsa, yayin da ake ambaton sa a cikin kiran salla da iƙama da tahiya da sauransu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Kwantar wa da Manzon Allah (ﷺ) hankali da tabbatar masa da cewa duk wata matsala da yake fuskanta daga mutanensa za ta gushe, nasara da rinjaye kuma suna tafe.

2. Duk wani tsanani da ƙunci akwai sauƙi tare da shi, matuƙar bawa yana tare da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Yana da kyau bawa ya ribaci lokutan da ayyuka suka yi masa sauƙi ya duƙufa wajen bautar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da roƙon sa kyakkyawan ƙarshe.

Suratus Sharh (5-8)

فَإِنَّ مَعَ ٱلۡعُسۡرِ يُسۡرًا ۝٥ إِنَّ مَعَ ٱلۡعُسۡرِ يُسۡرًا ۝٦ فَإِذَا فَرَغۡتَ فَٱنصَبۡ ۝٧ وَإِلَىٰ رَبِّكَ فَٱرۡغَب ۝٨

5. To lalle tsanani yana tare da sauƙi.

6. Lalle tsananin yana tare da sauƙi.

7. Saboda haka idan ka gama (harkokinka) sai ka kafu (wajen bautar Allah).

8. Sannan kuma ka yi kwaɗayi wajen Ubangijinka kawai.

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, tare da kowane tsanani da ƙunci, to akwai sauƙi da yalwa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma nanata cewa, lalle tare da tsananin da ƙuncin akwai sauƙi da yalwa, domin ya tabbatar masa da cewa, koyaushe yana tare da nasara da rinjaye mai ƙarfi, don haka kada muzgunawar mutanensa ta dame shi har ta hana shi aikinsa na kira zuwa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da cewa, idan ya gama ayyukansa na yau da gobe to ya sami isasshen lokaci ya ƙara sa ƙaimi wajen bautarsa, ya kuma nuna kwaɗayinsa gare shi (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rantsuwa da ɓaure da zaitun da wuraren fitowarsu, yana nufin garin Sham mahaifar yawancin annabawan Banu Isra'il, har ma da Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi). Rantsuwa da Dutsen Ɗuri Sinina kuma yana nuni zuwa ga wurin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi magana da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya ba shi littafin Attaura. Gari amintacce kuwa shi ne Makka inda aka haifi Manzon Allah Muhammadu ɗan Abdullahi (ﷺ), aka aiko shi da saƙo na ƙarshe. Wannan ya nuna waɗannan manyan addinan guda uku, watau addinin Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a

gare shi) da na Annabi Isa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) da na Annabi Muhammadu (ﷺ) su ne suka zo da koyarwar da ta yi daidai da halittar asali ta ɗan'adam, watau Tauhidi.

2. Yi wa ɗan'adam kyakkyawar halitta miƙaƙƙiya tare da ba shi hankali da zai bambance abubuwa masu amfani gare shi da marasa amfani wata babbar ni'ima ce a gare shi da ya wajaba a kansa ya yi wa Allah mahaliccinsa godiya a kanta, ya bauta masa shi kaɗai, ya bi umarninsa ya guje wa haninsa.

3. Duk sa'adda ɗan'adam ya butulce wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to lalle ya mayar da kansa mafi ƙasƙancin ƙasƙantattu.

4. Duk wanda ya zamanto yana aikata kyawawan ayyuka a lokacin ganiyar ƙarfinsa, sai tsufa ya cim masa ya hana shi aikata abin da ya saba aikatawa a baya, to zai ci gaba da samun ladansa cikakke ba tare da ya yanke ba.

5. Ba zai yiwu ba ga Allah mai hikima wanda ya halicci mutum cikin kyakkyawar sura, ya yi masa guzurin duk abin da rayuwarsa a duniya take buƙata, ya kuma hore masa hankali, sannan a ce ya bar shi hakanan kara-zube, ba tare da ya yi masa hisabi a kan ayyukansa masu kyau da munana ba.

95-Suratut Tin

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da suna '*Suratut Tin'*, amma akan kira ta da '*Suratu Wat-Tin'*. An kira ta da wannan suna ne saboda kalmar *'At-Tin'* ta zo a ayarta ta farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Mafi ingancin zance Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ishirin da takwas (28) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Buruj*' kafin '*Suratu Kuraish*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta takwas ne (8).

5. Babban Jigonta:
Tabbatar da cewa, darajar ɗan'adam tana tattare ne da riƙo da addinin Allah; idan ya saki addini, to ya fi komai ƙaskancewa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Hikimar Allah ta halittar ɗan'adam a kan kyakkyawar kama mai tsafta, daga baya ne yake kangarewa ya saɓa wa asalinsa.
• Hannunka-mai-sanda ga kafirai game da narkon Allah ga masu ƙaryata addininsa.
• Nuna wa ɗan'adam kyakkyawar halitta da Allah ya yi masa.

Suratut Tin (1-8)
وَٱلتِّينِ وَٱلزَّيْتُونِ ۝١ وَطُورِ سِينِينَ ۝٢ وَهَٰذَا ٱلْبَلَدِ ٱلْأَمِينِ ۝٣ لَقَدْ خَلَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ فِىٓ أَحْسَنِ تَقْوِيمٍ ۝٤ ثُمَّ رَدَدْنَٰهُ أَسْفَلَ سَٰفِلِينَ ۝٥ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمْ أَجْرٌ غَيْرُ مَمْنُونٍ ۝٦ فَمَا يُكَذِّبُكَ بَعْدُ بِٱلدِّينِ ۝٧ أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِأَحْكَمِ ٱلْحَٰكِمِينَ ۝٨

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da ɓaure da zaitun.

2. Da (dutsen) *Ɗuri Sinina*.

3. Da wannan garin amintacce (watau Makka).

4. Haƙiƙa Mun halicci mutum a kan mafi kyan diri.

5. Sannan Muka mayar da shi mafi ƙaskancin ƙaskantattu.

6. Sai fa waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, to su kam suna da lada ba mai yankewa ba.

7. To (kai kafiri) me ya sa kake ƙaryata ranar sakamako bayan haka?

8. Ashe Allah ba Shi ne Mafi iya hukuncin masu hukunci ba?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da wasu abubuwa guda huɗu:
Na farko, ya yi rantsuwa da bishiyar ɓaure, watau da wuraren tsurowarta.
Na biyu, ya yi rantsuwa da bishiyar zaitun, watau da wuraren tsurowarta.

Na uku, ya yi rantsuwa da Dutsen 'Ɗuri Sinina' inda Allah ya yi magana da Annabi Musa (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).
Na huɗu, ya yi rantsuwa da garin Makka mai alfarma, wanda duk wanda ya shige shi ya aminta daga duk wani tsoro.
Sannan sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana dalilin waɗannan rantse-rantse da cewa, lalle ya halicci ɗan'adam a kan mafi kyan diri da kamanni, sannan daga baya sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya mayar da shi tsoho tukuf a duniya har ya kasa amfana da gangar jikinsa, kamar yadda ba zai iya amfana da shi ba idan kyakkyawar halittarsa ta asali, watau fiɗira ta lalace, ya zamanto ɗan wuta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya togace wasu bayinsa waɗanda suka yi imani da shi da Manzonsa (ﷺ) suka yi kyawawan ayyuka, to waɗannan ko da sun tsufa tukuf, sun kasa ci gaba da aikata kyawawan ayyukan da suka saba, to suna da wani lada wanda ba ya yankewa har abada, shi ne gidan Aljanna, domin sun tsarkake asalin halittarsu ba su gurɓata shi da miyagun ayyuka ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna butulcin ɗan'adam kafiri yana tambayar sa dalilin da ya sanya yake ƙaryata ranar sakamakon ayyuka bayan duk wasu ƙwararan alamu masu nuna cikar Kudurar Allah a kan komai sun bayyana a gare shi. Shin bai san cewa kasancewar ranar alƙiyama ita ce ranar sakamako shi ya tabbatar da cewa, Allah shi ne ya fi duk wasu masu hukunci iya hukunci da tsayar da adalci ba? Don haka ta yaya wani zai yi tsammanin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai ƙyale bayinsa hakanan sakaka ba tare da ya yi hukunci a tsakaninsu, ya saka wa wanda ya kyautata da kyakkyawan sakamako, wanda kuma ya munana ya haɗa shi da mummunan sakamako ba?

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Waɗannan ayoyi biyar su ne farkon abin da aka yiwo wa Annabi (ﷺ) wahayinsa na Alƙur'ani, da su ne ya zama Annabin Allah.

2. Duk wani karatu ko ilimi wanda ba zai haɗa bawa da Ubangijinsa ba, ba kuma zai gadar masa da tsoron Allah ba, to wannan ilimi ne marar amfani ga ɗan'adam. Don haka kowane ilimi mutun zai koya, to ya sanya sunan Allah a ciki, kada kuma ya yarda ya raba shi da Ubangijinsa.

3. Wanda ya halicci mutum ya kula da shi da buƙatunsa, to dole ne a yi imani da kulawarsa gare shi, ta hanyar yi masa umarni da hani da aiko masa manzanni da saukar masa littattafai.

4. Babban karamcin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa ɗan'adam shi ne saukar masa da wahayi da sanar da shi ilimin abin da bai sani ba.

5. Falalar ilimi da muhimmancinsa, domin shi ne farkon abin da aka yi wa Manzon Allah (ﷺ) wahayi da shi, watau umartar sa da yin karatu.

6. Yawan karatu hanya ce ta samun ilimin abin da mutum bai sani ba.

7. Ishara ga al'ummar Larabawa waɗanda a lokacin ba sa rubutu ba sa karatu da cewa, ba da jimawa ba za su zama al'umma mai ilimi da za su cika duniya da rubuce-rubuce.

8. Ana samun ilimin komai ne ta hanyar koyon sa daga masanansa.

9. Muhimmancin rubuce-rubuce, domin ta haka ne ake tattara ilimi wuri guda kuma a kiyaye shi daga ɓacewa, sannan kuma ya shiga wurare da garuruwa masu nisa.

10. Tabbatar da cewa, Annabi (ﷺ) bai san Alƙur’ani ba kafin a yo masa wahayinsa, don haka aka kwantar masa da hankali da nuna masa cewa, kada ya fitar da tsammani, wanda ya koyar da mutane karatu da rubutu mai iko ne a kan ya koyar da shi Alƙur’ani, har ya zamanto makarancin sa ba tare da ya koyi rubutu ba.

96-Suratul Alaƙ

Mabuɗin Sura:

1.Sunanta:
A mafi yawan littattafan tafsiri da *mus'hafai* ana kiran ta ‘*Suratul Alaƙ’*. Amma ta shahara a zamanin sahabbai da suna ‘*Suratu Iƙra’a Bismi Rabbik’*.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Ita ce Surar da aka fara saukar wa Manzon Allah (ﷺ).

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta farko, kamar yadda ya tabbata a cikin littattafan hadisai da na sira, kuma wannan ita ce mafi ingancin magana ta malamai.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha tara ne (19) a lissafin mutanen Kufa da Basra. A wurin mutanen Sham kuwa goma sha takwas ne (18). Amma a lissafin mutanen Madina da Makka adadinsu ashirin ne (20) daidai.

5. Dalilin Saukarta:
A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ruwaito cewa, farkon abin da aka fara nuna wa Manzon Allah (ﷺ) shi ne mafarki, kuma duk sanda ya yi mafarki sai ya gan shi kamar hasken asuba. Sannan aka sanya masa son zama shi kaɗai, domin ya kasance yana fita zuwa kogon wani dutse a Makka da ake kira Dutsen *Hira;* yakan zauna shi kaɗai a wannan kogo tsawon wasu kwanaki har guzurin da ya fita da shi ya ƙare, sai ya dawo gida wurin Nana Khadija (Allah ya ƙara mata yarda) don ya sake tanadar wani guzurin. Yana cikin haka wata rana sai kawai Mala'ika Jibrilu ya zo kwatsam ba zato ba tsammani, ya ce wa Manzon Allah (ﷺ): "Yi karatu!" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ai ni ba mai karatu ba ne." Sai ya kama Annabi (ﷺ) ya matse shi har sai da ya wahala sannan ya sake shi ya ce masa: "Yi karatu!" Sai ya ce: "Ai ni ba mai karatu ba ne." Sai ya sake kama shi ya matse shi a karo na biyu, sannan ya sake shi ya ce: "Yi karatu!" Sai ya ce: "Ni ba mai karatu ba ne." Sai ya kama shi ya matse a karo na uku sannan ya sake shi ya ce: "Yi karatu da sunan Ubangijinka wanda ya yi halitta...." har zuwa ƙarshen aya ta 5. [Bukhari #3 da Muslim #160].

6. Babban Jigonta:
Mutum ba ya zama cikakken mutum sai ta hanyar ilimi wanda aka haɗa shi da sunan Allah, mai sanya bawa ƙanƙantar da kai ga Ubangijinsa. Rashin wannan kuwa nakasa ce gare shi.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Koya wa Manzon Allah (ﷺ) karatun Alƙur'ani lokacin da bai san karatu da rubutu ba.
• Nuna wa Manzon Allah (ﷺ) cewa al'ummarsa nan gaba za ta zama al'umma mai karatu da rubutu, watau mai alfahari da ilimi.
• Jan hankalinsa zuwa ga duba ga halittun Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), musamman halittar mutum mai cike da abin mamaki, wadda aka soma ta daga gudan jini.
• Kashedi ga wanda yake ta hanƙoron sai ya hana Manzon Allah (ﷺ) salla da kiran mutane zuwa ga gaskiya da shiriya.
• Nusantar da Manzon Allah (ﷺ) cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana sane da maƙiyansa, kuma lalle zai ba shi nasara a kansu, ya rusa duk wani shirinsu.
• Tabbatar da dugadugan Manzon Allah (ﷺ) a kan abin da ya zo masa na gaskiya da kusantar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da salla, kuma kada ƙarfin maƙiyansa ya dame, shi domin ƙarfin Allah ya zarce na kowa.

Suratul Alaƙ (1-5)
ٱقۡرَأۡ بِٱسۡمِ رَبِّكَ ٱلَّذِي خَلَقَ ۝١ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِنۡ عَلَقٍ ۝٢ ٱقۡرَأۡ وَرَبُّكَ ٱلۡأَكۡرَمُ ۝٣ ٱلَّذِي عَلَّمَ بِٱلۡقَلَمِ ۝٤ عَلَّمَ ٱلۡإِنسَٰنَ مَا لَمۡ يَعۡلَمۡ ۝٥

1. Ka yi karatu da sunan Ubangijinka, Wanda Ya yi halitta.

2. Ya halicci mutum daga gudan jini.

3. Ka yi karatu alhali Ubangijinka Shi ne mafi karamci.

4. Wanda Ya koyar ta (hanyar) alƙalami.

5. Ya koyar da mutum abin da bai sani ba.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da umartar Manzon Allah (ﷺ) ya yi karatu da sunan Ubangijinsa wanda ya halicci dukkan halittu. Ya halicci mutum daga gudan jini bayan a da yana ɗigon maniyyi.
Sannan ya sake umartar sa da ya karanta abin da aka yiwo masa wahayinsa na Alƙur'ani, ya kuma sani cewa, Ubangijinsa shi ne mafi karamci da babu wanda ya kai shi, saboda shi mai yawan kyauta ne da kyautatawa. Shi ne wanda ya koyar da ɗan'adam rubutu ta hanyar amfani da alƙalami, ya kuma sanar da shi abin da bai sani ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Idan wadata ta haɗu da rashin ilimi da tsoron Allah, takan gadar wa ɗan'adam ɗagawa da ƙetare iyaka.

2. Tabbatar da tashi bayan mutuwa, domin komawa ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa kowa hisabi a kan ayyukansa.

3. Yana daga cikin ayyukan kafirai su hana bautar Allah da yin ibada cikin kwanciyar hankali da nutsuwa.

4. Annabi (ﷺ) ya kasance yana yin salla tun kafin a farlanta salloli biyar a kullum.

5. Duk wanda zai hana yin salla, to ya hana bin shiriya ne, ya kuma hana bin umarni da taƙawa, watau bin dokokin Allah.

6. Duk mutumin da yake kan shiriya, watau ilmi mai amfani, yake yin kuma umarni da taƙawa, watau bin dokokin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), to ƙoƙarin hana shi ba za a yi nasara ba, kuma wahalar banza ce.

7. Hana aikin alheri siffa ce ta kafirai.

8. Falalar sujjada, domin a cikinta ne bawa ya fi kusanci da Ubangijinsa.

9. Duk ayyukan ɗa'a ga Allah suna ƙara kusanta bawa ga Ubangijinsa ne.

10. Yana da kyau matuƙa bawa ya dimanci kusantar Allah, musamman da yin salloli lokacin da yake fuskantar barazanar maƙiyansa.

11. Haramcin yin biyayya ga wanda yake hana bautar Allah da bin dokokinsa.

Suratul Alaƙ (6-19)

كَلَّآ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَيَطۡغَىٰٓ ٦ أَن رَّءَاهُ ٱسۡتَغۡنَىٰٓ ٧ إِنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلرُّجۡعَىٰٓ ٨ أَرَءَيۡتَ ٱلَّذِي يَنۡهَىٰ ٩ عَبۡدًا إِذَا صَلَّىٰٓ ١٠ أَرَءَيۡتَ إِن كَانَ عَلَى ٱلۡهُدَىٰٓ ١١
أَوۡ أَمَرَ بِٱلتَّقۡوَىٰٓ ١٢ أَرَءَيۡتَ إِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰٓ ١٣ أَلَمۡ يَعۡلَم بِأَنَّ ٱللَّهَ يَرَىٰ ١٤ كَلَّا لَئِن لَّمۡ يَنتَهِ لَنَسۡفَعَۢا بِٱلنَّاصِيَةِ ١٥ نَاصِيَةٖ كَٰذِبَةٍ خَاطِئَةٖ ١٦
فَلۡيَدۡعُ نَادِيَهُۥ ١٧ سَنَدۡعُ ٱلزَّبَانِيَةَ ١٨ كَلَّا لَا تُطِعۡهُ وَٱسۡجُدۡ وَٱقۡتَرِب ۩ ١٩

6. Tabbas! Lalle (jinsin) mutum haƙiƙa yana yin ɗagawa.

7. Don ya ga kansa yana cikin wadata.

8. Lalle kuma zuwa ga Ubangijinka ne makomar (taka) take.

9. Ka ba ni labarin wanda yake hana.

10. Bawa yayin da ya yi salla.

11. Ka ba ni labari idan (shi Bawan) ya kasance a kan shiriya.

12. Ko kuma ya yi umarni da taƙawa.

13. Ka ba ni labari idan (shi mai hanawar) ya ƙaryata ya kuma ba da baya.

14. Shin bai sani ba cewa lalle Allah Yana ganin (sa)?

15. A'aha! Tabbas idan bai hanu ba to za Mu ja shi ta makwarkwaɗar kai.

16. Makwarkwaɗar kai mai ƙaryatawa, mai aikata laifi.

17. To ya kirawo majalisar tasa.

18. Mu kuma lalle za Mu kirawo (mala'iku) zabaniyawa.

19. Faufau! Kada ka bi shi, ka kuma yi salla, ka kusanta (ga Allah).

A waɗannan ayoyi Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da abin da yake jefa ɗan'adam cikin girman kai da ɗagawa, watau lokacin da zai samu kansa cikin wadata ta dukiya ko matsayi ko mulki, sai ya manta cewa, makomarsa zuwa ga Ubangijinsa take a ranar alƙiyama inda zai ga sakamakon ayyukansa masu kyau da munana.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ɗagawar mutum takan kai shi har ya nemi hana wani yin salla, watau bautar Ubangijinsa ko da kuwa wanda yake hanawar yana kan shiriya daga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), yana ibadarsa da hujja da ilimi. Ko kuma ya zamanto yana yi wa mutane umarni da taƙawa, watau bin umarnin Allah da guje wa haninsa. Yanzu mutum irin wannan ya dace a hana shi abin da yake yi?
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) kuma ya bayyana cewa, yanzu ba abin mamaki ba ne a ce, shi mai hana a bauta wa Allah ya zamanto ya ƙaryata abin da Manzon Allah (ﷺ) ya zo da shi, ya bijire masa? Shin wannan ba zai ji tsoron Allah ba? Kuma har wa lau shi bai san cewa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana ganin abin da yake aikatawa ba ne?

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsoratar da shi cewa, al'amarin ba fa kamar yadda yake zato ne ba, tabbas har idan bai daina abin da yake yi ba, watau ƙaryata mai kira zuwa gaskiya da hana shi bautar Allah, to lalle Allah zai damƙi makwarkwaɗar kansa ya ja shi da ƙarfi zuwa wutar Jahannama, domin kuwa mai wannan makwarkwaɗar kai mutum ne maƙaryaci a maganganunsa, mai aikata laifuffuka, don haka ya cancanci azabar Allah wadda babu mai iya kare shi; idan kuwa yana tantama, to sai ya kirawo 'yan majalisarsa su zo su kuɓutar da shi daga shiga wuta, shi kuma Allah ya tabbatar masa cewa, zai kirawo nasa mala'ikun zabaniyawa masu tsaron wutar Jahannama, ƙarfafa masu kaushin hali halayya, waɗanda ba sa saɓa wa umarnin Allah, masu cika aiki ne, don haka sai ya ga wane ɓangare ne a cikin ɓangarori biyun ya fi ƙarfi da tsanani?

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya kasance yana salla, sai Abu Jahl ya zo ya ce masa: "Ba na hana ka wannan ba? Ba na hana ka ba?" Sai Annabi (ﷺ) ya juya ya daka masa tsawa. Sai Abu Jahl ya ce: "Kai ka san kuwa babu mai yawan 'yan majalisata?" Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da faɗarsa: "*To ya kirawo majalisar tasa, mu kuma za mu kirawo zabaniyawa*." Sai Ibnu Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Wallahi da a ce ya kirawo majalisar tasa, da kuwa zabaniyawan Allah sun cafke shi." [Tirmizi #3349 da Ahmad #2321, 3044].

Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar masa da cewa al'amarin ba yadda yake zato ne ba, ba zai iya cutar da wanda yake hana wa yin ibada da komai ba, don haka kada Manzon Allah (ﷺ) ya yi masa biyayya, ya ƙyale shi ya ci gaba da ibadarsa, ya yi ta sujjada ga Allah kuma ya kusance shi da ayyukan ɗa'a.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Abu Jahl ya tambayi jama'arsa cewa: "Shin Muhammadu yana zuwa gabanku ya riƙa dungura fuskarsa a cikin ƙasa?" Sai aka ce masa: E, yana yi. Sai ya ce: "Na rantse da gunkin Lata da Uzza idan ya kuskura na gan shi yana haka, to sai na tattaka wuyansa, ko na turbuɗe fuskarsa a cikin rairayi!" Sai Manzon Allah (ﷺ) ya zo ya shiga salla, sai ko Abu Jahal ya miƙe ya nufi inda yake da niyyar zai tattaka wuyan Manzon Allah (ﷺ), mutane ba su ankara ba sai suka gan shi ya juya da baya a guje yana kakkarewa da hannayensa. Sai aka tambaye shi: "Me ya faru da kai ne haka?" Sai ya amsa da cewa: "Ai abin da na gani tsakanina da shi wani gwalalo ne da wani abin tsoro mai wasu fukafukai." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Da ya kuskura ya matso kusa da ni, da mala'iku sun yi masa gunduwa-gunduwa." Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya saukar da waɗannan ayoyi har zuwa ƙarshen Sura. [Muslim #2797 da Ahmad #8831].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Lokacin da bawa ya fi kusa da Ubangijinsa shi ne lokacin da yake sujjada, don haka ku yawaita yin addu'a." [Muslim #482].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman matsayin Alƙur'ani a wurin Allah.

2. Bayanin lokacin da aka fara saukar da Alƙur'ani, watau cikin daren Lailatul-Kadari a watan Ramadana.

3. Falalar daren Lailatul-Kadari da ɗimbin alherin da yake cikinsa da bayanin cewa, ibada a cikinsa ta fi ibadar wata dubu da babu Lailatul-Kadari a cikinsu.

4. Kwaɗaitar da Musulmi a kan ribatar wannan dare da bautar Allah a cikinsa da ɗimbin alherin da bawa zai samu.

5. Bayanin darajar wannan al'umma da yadda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya keɓance su da wannan babbar falala da bai yi wa sauran al'ummu ba.

6. Fifikon Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) a kan sauran mala'iku.

7. A cikin daren Lailatul-Kadari ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yake kasafta duk wani abu da zai wakana a shekara. Imani da haka wani sashi ne na imani da Kaddara.

97-Suratul Kadr

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura an fi sanin ta da '*Suratul Kadr'*. Amma wasu magabata suna kiran ta da '*Suratu Inna Anzalnahu'*, wasu kuma su ce *'Suratu Inna Anzalnahu Fi Lailatil Kadr'*.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai suna cewa Sura ce *Makkiyya,* amma akwai ‘yan kaɗan masu ganin *Madaniyya* ce.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ashirin da biyar (25) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta sauka bayan ‘*Suratu Abasa’* kafin *‘Suratus Shams’*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta biyar ne (5) a lissafin mutanen Madina da Basra da Kufa. Amma a wurin mutanen Makka da Sham adadinsu shida ne (6).

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin darajar Alƙur’ani mai girma da falalar Lailatul-Kadari.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Bayanin falalar Alƙur’ani.
• Mayar da martani ga masu ganin Alƙur’ani ba saukakke ne daga Allah ba.
• Kwarzanta girman darajar lokacin da aka sauko da Alƙur’ani a cikinsa, watau daren Lailatul-Kadari, wanda a cikinsa ne mala’iku suke sauka.
• Kwaɗaitar da Musulmi game da neman daren Lailatul-Kadari da yin ibada a cikinsa.

Suratul Kadr (1-5)

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ١ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ٣ مَٰلِكِ يَوۡمِ ٱلدِّينِ ٤ إِيَّاكَ نَعۡبُدُ وَإِيَّاكَ نَسۡتَعِينُ ٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Lalle Mu Muka saukar da shi (Alƙur’ani) a daren Lailatul-Kadari (dare mai daraja).

2. Mene ne ya sanar da kai mece ce Lailatul-Kadari?

3. (Daren) Lailatul-Kadari ya fi wata dubu alheri.

4. Mala’iku da Jibrilu suna ta saukowa da dukkanin al’amura a cikinsa da izinin Ubangijinsu.

5. Aminci ne shi (daren dukkansa) har zuwa hudowar alfijir.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tabbatar da cewa, ya saukar da Alƙur’ani a daren Lailatul-Kadari cikin watan Ramadana, watau ya saukar da jimillarsa a sama ta kusa a cikin wannan daren, kamar yadda a cikinsa ne ya fara saukar da shi ga Manzon Allah (ﷺ) a Kogon Hira.

Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: “An saukar da Alƙur’ani a dunƙule lokaci guda daga Lauhul Mahfuzu zuwa Baitul-Izza a sama ta kusa, sannan ya sauka ga Annabi (ﷺ) guntu-guntu gwargwadon buƙata a cikin shekara ashirin da uku.” [Al-Hakim #4216, Ibn Abi Shaiba #30190].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, ko ya san irin yawan albarka da tarin alheri da ya sanya a cikin daren Lailatul-Kadari?

Sai ya bayyana masa cewa, wannan dare babban dare ne, domin kuwa ya fi wata dubu alheri, watau ga wanda zai yi sallolin dare a cikinta yana mai neman lada a wurin Allah.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Duk wanda ya yi tsayuwar dare a cikin Lailatul-Kadari yana mai imani da neman lada, to za a gafarta masa abin da ya gabata na zunubansa". [Bukhari #1910 da Muslim #760].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, mala'iku tare da Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) suna saukowa a cikinsa da duk wani abu da Allah ya ƙaddara na arziki da mutuwa da haihuwa da duk wani abu da zai faru a wannan shekarar. Suna kuma saukowa ne da izinin Ubangijinsu. Sannan ya bayyana cewa, shi wannan dare dukkansa mai albarka ne da aminci tun farkonsa har zuwa ƙarshensa, watau lokacin huduwar alfijir.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Annabi (ﷺ) ya ce: "Na ga dukkan mafarkanku sun haɗu a kan goman ƙarshe, don haka ku nemi wannan dare a cikin kwanaki mara na wannan goman." [Muslim #1165].

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku lalubi daren Lailatul-Kadari a kwanakin mara na goman ƙarshe na watan Ramadana." [Bukhari #2017 da Muslim #1169].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Duk waɗanda ba su yi imani da manzancin Annabi Muhammadu (ﷺ) ba daga Ma'abota littafi, watau Yahudawa da Nasara, to waɗannan kafirai ne, imaninsu da sauran annabawa da littattafai ba zai amfane su ba.

2. Mushirikai da ma'abota littafi kafin zuwan Manzon Allah (ﷺ) suna rayuwa ne cikin ɓata da ɗimuwa, suna zaton a kan gaskiya suke. To bayan aiko Manzon Allah (ﷺ) sai gaskiya ta bayyana gare su ƙarara, don haka sai wasu suka musulunta suka gaskata Annabi (ﷺ), wasu kuwa sai suka doge a kan ci gaba da zama cikin addinin da suka gada daga iyayensu, duk da cewa sun ga gaskiya ƙuru-ƙuru ta bayyana. Da wannan ne Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yanke musu hanzari.

3. Muhimmancin ikhlasi wajen bautar Allah, domin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ba ya karɓar aikin da babu ikhlasi a cikinsa.

4. Malamai da dama sun kafa hujja da aya ta 5 a kan cewa, ayyuka nagari suna daga cikin imani.

5. Kafirai su ne mafiya sharrin halittun Allah a bayan ƙasa; muminai kuma su ne mafiya alherin halittun Allah kakaf.

6. Tarayyar addinan Allah a kan bauta wa Allah shi kaɗai da bin wasu hukunce-hukuncen shari'a, abu ne da zai sanya dole a yi imani da annabci.

7. Tsoron Allah shi ne babban sanadin shiga Aljanna da samun yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

98-Suratul Bayyina

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
A wasu littattafan tafsiri da *masahifu* an kira ta da '*Suratul Bayyina'*. A wasu kuma da dama an kira ta '*Suratul Kayyima'*. Annabi (ﷺ) ya kira ta da '*Lam Yakunil Lazina kafaru'*.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa Ubayyu ɗan ka'ab (Allah ya ƙara masa yarda) : Lalle Allah ya umarce ni in karanta maka "Lam yakunil Lazina kafaru." Sai Ubayyu ya ce "Ya kuma kama maka sunana?" manzon Allah (ﷺ) ya ce: "E." Sai Ubayyu ya fashe da kuka. [Bukhari #3809 da Muslim #799].

2. Sanda aka saukar da ita:
Yawancin malamai suna ganin sura ce *madaniyya* amma akwai masu cewa *makiyya* ce . Maganar farko dai ta fi yawa ta kuma fi ƙarfi.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ɗari da ɗaya (101) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *'Suratuɗ Ɗalak'* kafin '*Suratul Hashri'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta takwas ne (8) a wurin yawancin malamai. Amma a wurin mutanen Basra ayoyinta tara ne (9).

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin matsayin manzancin Annabi (ﷺ) da bayyanarsa a fili da kamalar ɗabi'unsa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Gargaɗin ma'abota littafi da mushirikai game da ƙaryata Alƙur'ani da Manzon Allah (ﷺ).
• Fito da tufka-da-warwara ta mushirikai da ma'abota littafi waɗanda suka kasance suna jiran su ga wata bayyananniyar hujja kafin su yi imani. To yayin da hujjar ta zo musu sai suka kafirce mata.
• Karyata da'awarsu ta cewa, Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya wajabta musu su ci gaba da riƙo da addinansu.
• Yi musu narko da azabar lahira.
• Yabon waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, da yi musu alƙawarin samun ni'imar Aljanna ta har abada.

Suratul Bayyina (1-8)
لَمۡ يَكُنِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ مُنفَكِّينَ حَتَّىٰ تَأۡتِيَهُمُ ٱلۡبَيِّنَةُ ١ رَسُولٞ مِّنَ ٱللَّهِ يَتۡلُواْ صُحُفٗا مُّطَهَّرَةٗ ٢ فِيهَا كُتُبٞ
قَيِّمَةٞ ٣ وَمَا تَفَرَّقَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡهُمُ ٱلۡبَيِّنَةُ ٤ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ وَيُقِيمُواْ
ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُواْ ٱلزَّكَوٰةَۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلۡقَيِّمَةِ ٥ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ فِي نَارِ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَآۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ شَرُّ
ٱلۡبَرِيَّةِ ٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ خَيۡرُ ٱلۡبَرِيَّةِ ٧ جَزَآؤُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ
فِيهَآ أَبَدٗاۖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُۚ ذَٰلِكَ لِمَنۡ خَشِيَ رَبَّهُۥ ٨

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Waɗanda suka kafirta daga ma'abota littafi da mushirikai ba su zamanto masu barin abin da suke kai (na kafirci) ba har sai hujja bayyananniya ta zo musu.

2. (Watau) Manzo daga Allah da zai riƙa karanta (musu) takardu masu tsarki.

3. (Waɗanda) a cikinsu akwai hukunce-hukunce masu ƙima.

4. Waɗanda kuma aka bai wa littafi ba su rarraba ba sai bayan da hujja bayyananniya ta zo musu.

5. Ba a kuma umarce su ba sai don su bauta wa Allah suna masu tsantsanta addini gare Shi, suna masu kauce wa ɓarna, suna kuma tsayar da salla, kuma suna ba da zakka. Wannan kuwa shi ne addinin miƙaƙƙiyar hanya.

6. Lalle waɗanda suka kafirta daga ma'abota littafi da mushirikai suna cikin wutar Jahannama suna madawwama a cikinta. Waɗannan su ne mafiya sharrin halitta.

7. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, waɗannan su ne mafiya alherin halitta.

8. Sakamakonsu a wajen Ubangijinsu gidajen Aljanna ne na dawwama waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu suna madawwama a cikinsu har abada; Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi. Wannan kuma (sakamako ne) ga wanda ya ji tsoron Ubangijinsa.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da bayyana cewa, kafirai daga cikin Yahudawa da Nasara da mushirikan Larabawa, ba su zamanto masu barin kafircinsu da suka haɗu a kai ba har sai wata hujja bayyananniya ta zo musu.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wannan hujjar da cewa, wani manzo ne da zai aiko yana karanta musu wasu takardu masu tsarki, watau waɗanda shaiɗanu ba sa iya shafar su sai dai mala'iku masu tsarki. A cikinsu kuma akwai labarai na gaskiya da hukunce-hukunce na adalci waɗanda suke ɗora mutane a kan miƙaƙƙen tafarki na gaskiya.
Wannan shi ne halin da suke ciki kafin aiko Manzon Allah (ﷺ), wai suna dakon zuwan sa, domin ya zo su yi imani da shi. Bayan zuwansa kuma sai suka rarrabu, wasu suka yi imani; wasu kuma suka ci gaba da kafircinsu, suka ƙaryata shi da duk abin da ya zo da shi.
Wannan ya sa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, Yahudawa da aka ba su littafin Attaura da Nasara da aka ba su littafin Linjila ba su rarraba ba sai bayan da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da Annabinsa (ﷺ), daga cikinsu wasu suka musulunta, wasu kuma suka doge a kan kafircinsu, tare da sun tabbatar shi mai gaskiya ne.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna cewa, abin da zai ƙara fito da taurin kan ma'abota littafi a fili shi ne cewa, babu wani umarni da aka yi musu a cikin Alƙur'ani wanda ya saba irin umarnin da aka yi musu a littattafansu na cewa, su bauta wa Allah shi kaɗai su guje wa shirka, su kuma tsayar da salla su bayar da zakka. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, wannan fa shi ne addinin miƙaƙƙiyar hanya wadda babu karkata a cikinta.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mummunan sakamakon waɗanda suka kafirta daga Yahudawa da Nasara da mushirikai, inda ya tabbatar da cewa, za su shiga wutar Jahannama a ranar alƙiyama su kuma dawwama a cikinta har abada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya siffanta ta su da cewa, su ne mafi sharrin halittu, saboda kafircinsu da yadda suka ƙaryata Manzon Allah (ﷺ).
Su kuma waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa (ﷺ) suka kuma yi ayyuka nagari, to waɗannan su ne mafiya alherin halittu, domin kuwa sakamakonsu a wajen Ubangijinsu shi ne gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za su shige su su kuma dawwama a cikinsu har abada. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yarda da su saboda sun yi imani da shi sun yi masa ɗa'a, su ma kuma sun yarda da shi saboda cikakkiyar rahamarsa da suka samu. Wannan rahama ta Allah kuwa, sakamako ne ga duk wanda ya ji tsoron sa ya bi umarninsa ya kuma guje wa haninsa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Rikirkicewar tsarin gudanar duniya yayin tsayuwar alƙiyama.

2. Ɗimaucewar kafiri lokacin da zai ga wasu abubuwan ban tsoro suna ta faruwa ba zato ba tsammani.

3. Kasa za ta ba da shaida a kan ayyukan da mutane suka aikata a kanta.
4. Kwaɗaitarwa a kan aikin alheri komai ƙanƙantarsa da tsoratarwa game da aikata sharri komai ƙanƙantarsa.

99-Suratuz Zalzala

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Yawancin magabata sun kira ta da *'Suratu Iza Zulzilat'*.
An karɓo daga Mu'azu ɗan Abdullahi Al-Juhani (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na ji wani mutum ɗan ƙabilar Juhaina yana cewa: "Ya ji Manzon Allah (ﷺ) yana karanta *'Iza Zulzilatil Ardhu'* a sallar asuba, a duka raka'o'inta biyu.
A cikin wasu tafsirai an kira ta '*Suratuz Zilzaal*'.

Muƙatil ɗan Sulaiman ya kira ta ‘*Suratuz Zalzala’* kamar yadda yake a cikin *Mus'hafin* da ke hannuwanmu.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai suna ganin Sura ce *Madaniyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta tis’in da huɗu (94) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta sauka bayan ‘*Suratun Nisa’i’* kafin *‘Suratul Hadid’*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta takwas ne (8) a wurin mutanen Kufa. Amma a wurin yawancin malamai lissafin ayoyi, ayoyinta tara ne (9).

5. Babban Jigonta:
Tana tabbatar da zuwan alƙiyama da hisabin ayyukan bayi masu kyau da munana.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tabbatar da tashin alƙiyama da aukuwar wasu alamominta da firgitar mutane yayin faruwansu.
• Fitowar mutane domin gudanar da hisabin ayyukansu masu kyau da munana, manya da ƙanana.

Suratuz Zalzala (1-8)
إِذَا زُلۡزِلَتِ ٱلۡأَرۡضُ زِلۡزَالَهَا ۝١ وَأَخۡرَجَتِ ٱلۡأَرۡضُ أَثۡقَالَهَا ۝٢ وَقَالَ ٱلۡإِنسَٰنُ مَا لَهَا ۝٣ يَوۡمَئِذٖ تُحَدِّثُ أَخۡبَارَهَا ۝٤ بِأَنَّ رَبَّكَ أَوۡحَىٰ لَهَا ۝٥ يَوۡمَئِذٖ يَصۡدُرُ ٱلنَّاسُ أَشۡتَاتٗا لِّيُرَوۡاْ أَعۡمَٰلَهُمۡ ۝٦ فَمَن يَعۡمَلۡ مِثۡقَالَ ذَرَّةٍ خَيۡرٗا يَرَهُۥ ۝٧ وَمَن يَعۡمَلۡ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖ شَرّٗا يَرَهُۥ ۝٨

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Idan aka girgiza ƙasa matuƙar girgiza ta.

2. Kasar kuma ta fitar da nauyaye-nauyayenta.

3. Mutum kuma ya ce: “Me ya same ta?”

4. A wannan ranar ne za ta ba da labaranta.

5. Don Ubangijinka Ya umarce ta (da yin haka).

6. A wannan ranar mutane za su fito a warwatse, don a nuna musu ayyukansu.

7. To duk wanda ya yi aikin alheri daidai da zarra zai gan shi.

8. Wanda kuma duk ya yi aikin sharri daidai da zarra zai gan shi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da ba da labarin lokacin tashin alƙiyama, watau yayin da ƙasa za ta yi matuƙar girgiza ta fitar da matattun da suke cikinta da sauran ma'adanan ƙarƙashinta. A lokacin mutum zai ɗimauce ya riƙa cewa, me ya same ta ne take wannan girgiza mai tsanani?

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Kasa za ta amayo 'ya'yan cikinta (manya-manya) kamar dirkoki na zinari da azurfa, sai wanda ya yi kisa ya zo ya ce: 'A kan wannan ne na yi kisa'; sai mai yanke zumunci ya zo yana cewa: 'A kan wannan ne na yanke zumuncina'; sai ɓarawo shi ma ya zo ya ce: 'A kan wannan ne aka yanke mini hannuna'. Sannan sai su duka su bar wannan dukiya ba tare da sun ɗauki komai daga cikinta ba." [Muslim #1013 da Tirmizi #2208].

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a wannan rana ce ƙasa za ta ba da labaran ayyukan da aka aikata a kanta na alheri ko na sharri, domin Allah Ubangijinta ya umarce ta da yin haka, don haka ba za ta saɓa umarninsa ba.
Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, a wannan rana ce mai tsanani da abin tsoro, mutane za su fito zuwa wurin hisabi ƙungiya-ƙungiya, domin a nuna musu ayyukansu masu kyau da munana, waɗanda suka aikata a duniya.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana sakamakon kowa da cewa, duk wanda ya yi wani aikin alheri gwargwadon 'zarra', watau daidai da nauyin jaririyar tururuwa, to zai ga aikinsa a gabansa. Hakanan duk wanda ya yi wani aikin sharri gwargwadon 'zarra', watau daidai da nauyin jaririyar tururuwa, to zai gan shi a gabansa.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: An tambayi Manzon Allah (ﷺ) cewa: Ya Manzon Allah, mene ne hukuncin zakkar jakai? Sai ya ce: "Ba a saukar mini da komai ba dangane da jakai, sai wannan gamammiyar ayar cewa: "*Wanda ya yi aikin alheri daidai da zarra zai gan shi. Wanda kuma duk ya yi aikin sharri daidai da zarra zai gan shi*." [Bukhari #2371 da Muslim #987].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Falalar dawakai waɗanda aka tanade su domin fita yaƙin ɗaukaka kalmar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Jan hankali ga masu tanadar dawakai da nuna musu cewa, ana son kiwata dawakai ne da ba su kyakkyawan horo don a fita da su wajen ɗaukaka addinin Allah. Ba kawai a ajiye su don alfahari da nuna isa ko kwalliya ba, domin yin haka alama ce ta 'yan duniya, ba mutane masu tunanin lahirarsu ba.

3. Mummunar ɗabi'ar ɗan'adam ta tsananin butulce wa ni'imar Allah, wanda haka ne yake jefa shi cikin tsananin rowa da maƙo, sai fa ga wanda Allah ya saka masa tsoron sa a zuciya.

4. Yawan tunanin ranar lahira yakan rage wa ɗan'adam tsananin son abin duniya da ɗabi'ar nan ta rowa da dukiya.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya haɗa tsakanin ƙaburbura da zukata, domin zuciyar ɗan'adam ita ce take ɓoye abin da yake cikinta na alheri ko na sharri, ƙabari kuwa shi ne yake rufe gangar jikinsa yayin da ya mutu. To a ranar lahira sai Allah ya fito da gangar jikin tasa daga ƙabarinsa, ya bankaɗo sirrin da ke cikin zuciyarsa, sai ya zamanto gangar jikinsa ta fito sarari a bayan ƙasa, sirrinsa kuma ya bayyana a fili a kan fuskarsa yadda kowa zai gane.

100-Suratul Adiyat

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
An fi sanin wannan Sura da '*Suratul Adiyat*'. Amma a wasu littattafan tafsiri an kira ta da '*Suratu Wal-Adiyat*'. Watau an yi mata suna da kalmar farko da ta zo a cikinta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:

Sura ce *Makkiyya* a wurin yawancin malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma sha huɗu (14) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Asri'* kafin '*Suratul Kausar*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha ɗaya ne (11).

5. Babban Jigonta:
Tana nuna tsananin son abin duniya da ke tare da ɗan'adam da tunatar da shi makomarsa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Falalar dawakan mayaƙa masu ɗaukaka kalmar Allah.
• Sukar ɗabi'ar ɗan'adam ta butulci ga Ubangijinsa da tsananin son abin duniya.
• Tunatar da mutane cewa, akwai ranar komawa ga Allah don yin hisabi, kuma duk abin da suke yi Allah yana ganin su.

Suratul Adiyat (1-11)
وَٱلۡعَٰدِيَٰتِ ضَبۡحٗا ١ فَٱلۡمُورِيَٰتِ قَدۡحٗا ٢ فَٱلۡمُغِيرَٰتِ صُبۡحٗا ٣ فَأَثَرۡنَ بِهِۦ نَقۡعٗا ٤ فَوَسَطۡنَ بِهِۦ جَمۡعًا ٥ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لِرَبِّهِۦ لَكَنُودٞ ٦ وَإِنَّهُۥ
عَلَىٰ ذَٰلِكَ لَشَهِيدٞ ٧ وَإِنَّهُۥ لِحُبِّ ٱلۡخَيۡرِ لَشَدِيدٌ ٨ ۞أَفَلَا يَعۡلَمُ إِذَا بُعۡثِرَ مَا فِي ٱلۡقُبُورِ ٩ وَحُصِّلَ مَا فِي ٱلصُّدُورِ ١٠ إِنَّ رَبَّهُم بِهِمۡ يَوۡمَئِذٖ
لَّخَبِيرُۢ ١١

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da (dawaki) masu sukuwa suna kukan ciki.

2. Sannan masu bugun ƙyastu da kofatai.

3. Sannan masu kai hari da asuba.

4. Sai suka tayar da ƙura da ita (sukawar tasu).

5. Sai kuma suka shiga tsakiyar taro (da mahayansu)

6. Lalle mutum tabbas mai yawan butulci ne ga Ubangijinsa.

7. Lalle kuma shi shaida ne a kan haka.

8. Lalle shi kuma mai tsananin son alheri ne.

9. Shin bai sani ba ne idan aka bankaɗo abubuwan da suke cikin ƙaburbura?

10. Aka kuma tattaro abubuwan da suke cikin ƙiraza?

11. Lalle a wannan ranar tabbas Ubangijinsu Masani ne game da su.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da dawakai waɗanda ya siffanta su da cewa masu sukuwa ne suna kukan ciki saboda tsananin gudu. Masu kuma ƙyasta wuta da kofatansu idan suka daki duwatsu da su, saboda tsananin dirarsu. Kuma masu kai wa maƙiya hari lokacin asuba. Da wannan tsananin gudun ne kuma suke tayar da ƙura, sannan su kutsa tsakiyar taron maƙiya da mahayansu, don su tarwatsa su.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana wata mummunar ɗabi'a ta ɗan'adam da cewa, shi mai tsananin butulce wa ni'imomin Ubangijinsa ne, ba ya gode masa, kuma ba ya yi wa wani alheri da abin da Allah ya ba shi, shi kansa kuma shaida ne a kan wannan butulci da rowar tasa, sannan kuma ga shi mai tsananin son dukiya, wanda hakan ne yake sanya shi rowa da mammaƙo.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya gargaɗe shi inda ya ja hankalinsa da cewa, shin bai sani ba ne idan Allah ya tashi matattun da suke cikin ƙaburbura, ya fito da su domin yi musu hisabi, ya kuma bayyana abin da yake cikin zukata na aƙidu da niyyoyi? To a lokacin ne ɗan'adam zai gane cewa, lamarin ya fi ƙarfin yadda yake zato, domin zai tabbatar da cewa, lalle Ubangijin bayi a wannan rana masanin komai ne ciki da waje, babu abin da zai ɓuya gare shi, kuma zai yi wa kowa sakayya a kan ayyukansa masu kyau ko munana.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama.

2. Tabbatar da cewa, ranar alƙiyama rana ce mai cike da abubuwan ban tsoro, waɗanda za su ƙwanƙwasa zukata da tsoronsu.

3. A ranar alƙiyama mutane za su tarwatse kowa ya kama gabansa, yana ta kansa.

4. Tabbatar da ma'aunin ayyuka a ranar aƙiyama.

5. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai yi wa bayinsa sakamako ne bisa la'akari da abin da ya fi rinjaye na aikinsu, idan mai kyau ne ya rinjayi mummuna sai bawa ya sami kyakkyawar makoma, a yafe masa munanan ayyukansa. Idan kuwa munanan ayyukansa ne suka yi rinjaye, to makomarsa wutar Jahannama ne. Wannan yana nuna falalar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga bayinsa muminai da kuma cikar adalcinsa ga masu laifi.

101-Suratul Kari’a

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta fi shahara ne da ‘*Suratul Kari’a’*, domin da wannan kalma ne ‘*Al-Kari’a’* aka buɗe ta.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:

Ita ce Sura ta talatin (30) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratu Kuraish'* kafin '*Suratul Kiyama'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta goma sha ɗaya ne (11) a lissafin mutanen Kufa. Amma a lissafin mutanen Madina da Makka ayoyinta goma ne (10). A wurin mutanen Sham da Basra kuma ayoyinta takwas ne (8).

5. Babban Jigonta:
Tana ƙwanƙwasa zukata ne don ta sa musu tsoron ranar alƙiyama.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tabbatar da zuwan ranar alƙiyama da abubuwan ban tsoro da za su rigayi zuwanta.
• Tabbatar da sakamakon ayyuka masu kyau da munana.
• Tabbatar da awon ayyukan bayi a ranar alƙiyama.

Suratul Ƙari'a (1-11)
ٱلۡقَارِعَةُ ۝١ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ۝٢ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ۝٣ يَوۡمَ يَكُونُ ٱلنَّاسُ كَٱلۡفَرَاشِ ٱلۡمَبۡثُوثِ ۝٤ وَتَكُونُ ٱلۡجِبَالُ كَٱلۡعِهۡنِ ٱلۡمَنفُوشِ ۝٥ فَأَمَّا
مَن ثَقُلَتۡ مَوَٰزِينُهُۥ ۝٦ فَهُوَ فِي عِيشَةٖ رَّاضِيَةٖ ۝٧ وَأَمَّا مَنۡ خَفَّتۡ مَوَٰزِينُهُۥ ۝٨ فَأُمُّهُۥ هَاوِيَةٞ ۝٩ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا هِيَهۡ ۝١٠ نَارٌ حَامِيَةُۢ ۝١١

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Mai ƙwanƙwasa (zukata da tsoro).

2. Mece ce mai ƙwanƙwsa (zukata da tsoro)?

3. Kuma me ya sanar da kai mece ce mai ƙwanƙwasa (zukata da tsoro)?

4. (Ita ce) ranar da mutane za su zama kamar ɗangon fari masu bazuwa.

5. Duwatsu kuma su zama kamar kaɗaɗɗiyar auduga.

6. To amma wanda maʾaunan ayyukansa suka yi nauyi.

7. To shi kam yana cikin rayuwa mai gamsarwa.

8. Amma kuma duk wanda maʾaunan ayyukansa suka yi shafal.

9. To shi makomarsa (wutar) *Hawiya* ce.

10. Kuma me ya sanar da kai mece ce ita?.11. Wuta ce mai tsananin zafi.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da kiran ranar alƙiyama da wani suna, watau '*al-Ƙari'a'* wanda yake nufin mai ƙwanƙwasa zukata da tsoro. Sai kuma ya nuna girman shaʾaninta inda ya yi tambaya cewa, mece ce mai ƙwanƙwasa zukata da tsoro? Ya kuma tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, mene ne ya sanar da shi me ake kira da mai ƙwanƙwasa zukata da tsoro?

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana ranar da cewa, ita ce ranar da mutane za su zama kamar ɗangon fara masu bazuwa a ko'ina. Duwatsu kuma su zama kamar kaɗaɗɗiyar auduga saboda rashin nauyinsu da watsewarsu a cikin sararin sama. To kamar haka ne mutane za su tarwatse a wannan rana, saboda tsananin tsoro da firgici su warwatsu a ko'ina da ina, kowa yana ta kansa.
Sai kuma Allah ya bayyana sakamakon mutane a wannan rana yayin da za su kasu kashi biyu:
Kashi na farko, su ne waɗanda kyawawan ayyukansu za su rinjayi munana, to waɗannan suna cikin rayuwa mai gamsarwa a gidan Aljanna.
Kashi na biyu, su ne waɗanda idan aka auna ayyukansu za su yi shafal ba nauyi, watau munanan ayyukansu za su rinjayi kyawawa; to waɗannan makomarsu a wannan rana ita ce wutar *Hawiya*, watau Jahannama, ita kuwa wuta ce mai tsananin zafi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Wutar da ɗan'adam yake hurawa kaso ɗaya ce daga cikin kaso saba'in na wutar Jahannama." Sahabbai suka ce: "Ya Manzon Allah, ai ko ta duniya ma ta isa azaba." Sai ya ce: "Ta lahira ta fi ta da kaso sittin da tara." [Bukhari #3265 da Muslim #2843].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tara dukiya ba shi ne abin zargi ba; abin zargi shi ne dukiya ko 'ya'ya ko matsayi su shagaltar da mutum ya manta da ɗa'ar Allah da tunanin lahira.

2. Zaman ƙabari zama ne na wucin-gadi ba na har abada ba, shi ya sa aka kira shi da ziyara ba zama ba, wannan ya tabbatar da tashi bayan mutuwa domin yin hisabi da sakamako a kan ayyuka.

3. Ilimi na haƙiƙa wanda yake ratsa zuciya shi ne ilimin da yake hana bawa yin alfahari da yawan abin da ya mallaka na duniya, yake zaburar da shi domin yin aikin da zai amfane shi a lahira.

4. Ranar alƙiyama rana ce da za a yi wa mutane tambaya a kan ni'imar da aka ba su a duniya.

102-Suratut Takasur

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta fi shahara da '*Suratut Takasur*' kamar yadda ya zo a cikin yawancin littattafan tafsiri da *masahifu*.
Ana kuma kiran ta da '*Suratu Al-Hakum*' kamar yadda ya zo a cikin S*ahihul Bukhari*.

Ya zo cewa sahabban Manzon Allah (ﷺ) suna kiran ta da '*Suratul Maƙbara'* domin a cikinta ne lafazin '*Al-Maƙabir'* ya zo, watau maƙabartu.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai suna ganin cewa Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma sha shida (16) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Kausar'* kafin '*Suratul Ma'un'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta takwas ne (8).

5. Babban Jigonta:
Tana jan kunnen mutane a kan kada su bari duniya ta shagaltar da su har su manta da lahira.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Gargaɗin mutane da tsawatar musu a kan cewa kada su bari duniya da ƙyale-ƙyalenta na tara dukiya da 'ya'ya su shagaltar da su su daina tunanin mutuwa da ranar lahira, har mutuwar ta zo musu ba zato ba tsammani su wayi gari a maƙabarta.
• Kwaɗaitar da su a kan su yi wa kansu tanadin abin da zai kuɓutar da su daga wutar Jahannama.
• Tunatar da su cewa, za a tashe su a ranar alƙiyama kuma za a yi musu hisabi game da ni'imar da aka yi musu ba su gode ba.

Suratut Takasur (1-8)
أَلۡهَىٰكُمُ ٱلتَّكَاثُرُ ١ حَتَّىٰ زُرۡتُمُ ٱلۡمَقَابِرَ ٢ كَلَّا سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ٣ ثُمَّ كَلَّا سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ٤ كَلَّا لَوۡ تَعۡلَمُونَ عِلۡمَ ٱلۡيَقِينِ ٥ لَتَرَوُنَّ ٱلۡجَحِيمَ ٦
ثُمَّ لَتَرَوُنَّهَا عَيۡنَ ٱلۡيَقِينِ ٧ ثُمَّ لَتُسۡـَٔلُنَّ يَوۡمَئِذٍ عَنِ ٱلنَّعِيمِ ٨

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Alfahari da yawan ('ya'ya da dukiya) ya shagaltar da ku.

2. Har kuka (mutu kuka) ziyarci ƙaburbura.

3. A'aha! (haka bai kamace ku ba) da sannu za ku sani.

4. Sannan a'aha, da sannu za ku sani.

5. Tabbas da za ku yi sani, sani na sakankancewa.

6. Tabbas haƙiƙa za ku ga wutar Jahimu.

7. Sannan tabbas haƙiƙa za ku gan ta gani da ido na sakankancewa.

8. Sannan kuma tabbas lalle za a tambaye ku a wannan ranar game da ni'imomin (da kuka mora a duniya).

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tsawatar wa mutane game da yadda alfahari da tara ‘ya’ya da dukiya ya shagaltar da su daga bin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), suka doge a kan haka har sai da suka mutu suka shiga ƙaburburansu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Ba talauci nake ji muku tsoro ba; ina ji muku tsoron alfahari da tara dukiya; ba kuma kuskure nake ji muku tsoro ba, ina ji muku tsoron ganganci ne.” [Ahmad #8074 da Ibn Hibban #3222 da Hakim #3970].

Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna musu cewa, bai dace a ce irin wannan mummunar ɗabi’a ta alfahari da tarin dukiya ko ‘ya’ya ta ɗauke musu hankali ba har su kai ga barin ɗa’ar Allah, domin ba da jimawa ba za su san rashin amfanin abin da suka yi. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu da cewa, tabbas da sun san za a tashe su a gaban Allah, ya yi musu hisabi da sakayya a kan ayyukansu, to da lalle ba su shagala da tara dukiya da alfahari da ‘ya’ya ba.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar musu cewa, lalle babu makawa sai sun ga wuta a ranar alƙiyama, gani kuma na sakankancewa wanda babu kokwanto ko kaɗan a cikinsa.
Ya kuma ya tabbatar musu cewa, lalle ba makawa sai an tambaye su a ranar alƙiyama game da ni’imomin da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu, kamar ni’imar lafiya ko ta wadata da makamantansu.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Bawa yakan ce: “'Dukiyata, dukiyata', alhali abu uku ne kawai nasa a cikin dukiyarsa; abin da ya ci ya ƙarar, da tufar da ya sa ya kashe, da abin da ya bayar sadaka ya yi wa kansa ajiya. Duk abin da ba waɗannan ba, to zai tafi ne ya bar wa mutane.” [Muslim #2959].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Shikkhir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Na je na sami Manzon Allah (ﷺ) yana karanta wannan Surar, yana cewa: “Ɗan’adam yana cewa, 'Dukiyata, dukiyata', shin kana da wani abu ne a dukiyarka in ban da wanda ka ci ka ƙarar, ko ka sanya a jikinka ka kashe, ko ka yi sadaka ka zartar?” [Ahmad #16305 da Muslim #2958].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: “Farkon ni’imar da za a tambayi bawa a kanta ranar alƙiyama shi ne za a ce masa: “Yanzu ashe ba mu ba ka lafiyar jiki ba? Muka kuma ƙosar da kai da ruwan sanyi?” [Tirmizi #3652 da Ibnu Hibban #7364 da Al-Hakim #7203].

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wata rana Manzon Allah (ﷺ) ya fita sai ya haɗu da Abubakar da Umar a hanya, sai ya tambaye su ya ce: “Me ya fito da ku a wannan lokaci daga gidajenku?” Sai suka ce: “Yunwa, ya Manzon Allah.” Sai ya ce: “Na rantse da Allah, abin da ya fito da ku ni ma shi ne ya fito da ni, don haka ku taso.” Sai suka tashi, sai suka zo gidan wani mutumin Madina amma sai suka samu ba ya nan. Lokacin da matarsa ta ga Manzon Allah (ﷺ) sai ta ce: “Maraba lale-lale.” Sai Manzon Allah (ﷺ) ya tambaye ta, ina mai gidanta ya tafi? Sai ta amsa da cewa: “Ya tafi ya nemo mana ruwan sha.” Suna tsaye sai ga wannan mutum ya dawo, yana ganin Manzon Allah (ﷺ) da sahabbansa su biyu sai ya ce: “Na gode wa Allah, a yau babu wanda ya kai ni manyan baƙi.” Sai nan take ya fita ya je ya samu hantsar dabino burarre da nunanne, sai ya ce: “Ku ci wannan.” Sai ya ɗauki wuƙa, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce masa: “Kada ka kuskura ka yanka dabbar tatsa.” Sai ya yi musu yanka suka ci naman wannan akuya suka ci dabino, suka sha nono. Bayan sun ci sun ƙoshi, sun sha ruwa sun yi nak, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce wa Abubakar da Umar: “Na rantse da wanda raina yake a hannunsa, tabbas sai an yi muku tambaya game da wannan ni’imar a ranar alƙiyama.” [Muslim #2038].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana rantsuwa da duk abin da ya ga dama a cikin halittarsa. Bai halatta Musulmi ya yi rantsuwa da komai ba sai da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Nuna muhimmancin lokaci wanda a cikinsa mumini yake ribatar zamansa na duniya wajen neman yardar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

3. Imani da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da aikata kyawawan ayyuka su ne suke sanya bawa ya samar wa kansa kamala.

4. Yi wa juna wasiyya da bin gaskiya da yin haƙuri, da su ne kuma mumini yake samar wa ɗan'uwansa kamala.

5. Aiwatar da waɗannan al'amura huɗu ne suke kuɓutar da bawa daga faɗawa cikin asara ta duniya da ta lahira, suke kuma sanya shi ya ci ribar rayuwarsa ta duniya.

6. Kira zuwa ga gaskiya yana buƙatar juriya da haƙuri. Hakanan riƙo da gaskiya yana buƙatar juriya da haƙuri.

103-Suratul Asr

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta fi shahara da '*Suratul Asr*', amma a wasu littattafan tafsiri da *Sahihul Bukhari* an kira ta '*Suratu Wal-Asr*'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce Makkiyya.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma sha uku (13) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratus Sharhi*' kafin *'Suratul Adiyat'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta uku ne (3).

5. Falalarta:
An karɓo daga Abu Madina Ad-Darimi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: "Idan mutum biyu daga cikin sahabban Manzon Allah (ﷺ) suka haɗu, to ba za su rabu ba har sai ɗaya ya karanta wa ɗayan *'Suratul Asri'*, sannan su yi sallama da juna". [Abu Dawud, *Az-Zuhd* #402 da Ɗabarani, *Al-Ausaɗ* #5124 da Baihaƙi, *Shu'abul Iman* #8639].

6. Babban Jigonta:
Duk rayuwar ɗan'adam asara ce idan babu bin Allah a cikinta.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tabbatar da tsananin asara ga waɗanda suka kafirce wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) suka rungumi saɓon Allah.
• Tabbatar da tsira ga muminai masu kyawawan ayyuka, masu kira zuwa ga gaskiya.
• Falalar haƙuri a kan bin gaskiya da kauce wa ƙarya da jajircewa a kan haka.

Suratul Asr (1-3)

وَٱلۡعَصۡرِ ۝١ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَفِي خُسۡرٍ ۝٢ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡحَقِّ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ ۝٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da zamani.

2. Lalle mutum yana cikin asara.

3. Sai dai waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, suka kuma yi wa juna wasiyya da gaskiya, suka kuma yi wa juna wasiyya da haƙuri.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da rantsuwa da zamani wanda ya ƙunshi dare da rana waɗanda su ne mahallin dukkan ayyukan bayi. Ya yi wannan rantsuwa ne kuwa domin ya tabbatar da cewa, duk wani ɗan'adam yana cikin asara a rayuwa, kowa da gwargwadon tasa asarar.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya togace wasu bayinsa daga aukawa cikin wannan asara, su ne kuwa waɗanda suka siffantu da siffofi huɗu:
Siffa ta farko, imani da Allah da duk abin da ya umarci bawa ya yi imani da shi, wanda hakan ba zai yiwu ba sai da ilimin sanin Allah.
Siffa ta biyu, aiki na ƙwarai, wannan kuwa ya ƙunshi duk ayyukan alheri na sarari da na ɓoye; masu alaƙa da haƙƙoƙin Allah, da masu alaƙa da haƙƙoƙin bayinsa, na wajibai ko na mustahabbai.

Siffa ta uku, yi wa juna wasiyya da gaskiya, wadda ita ce kwaɗaitar da juna a kan yin imani da yin aiki nagari.
Siffa ta huɗu, yi wa juna wasiyya a kan haƙuri wajen bin Allah da barin saɓa masa, da haƙuri da ƙaddararsa marar daɗi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Haramcin zunɗen mutane da aibata su.

2. Tara dukiya da yin rowa da ita, suna daga cikin abubuwan da suke sanya wasu su riƙa sukan mutane suna aibata su, domin suna ganin duk wanda bai tara dukiya irin tasu ba, to bai cancanci su girmama shi ba, don haka sai wannan ya gadar musu da girman kai.

3. Tsananin son tara dukiya da taskake ta yakan sanya wa mutum jin cewa kamar ba zai mutu ba, domin a zatonsa yana da abin da zai magance masa kowace irin matsala ta rayuwa da za ta taso masa, saboda haka sai ya shiga aiki irin na mutumin da bai yarda da akwai mutuwa ba.

4. Wutar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) zai jefa kafirai wuta ce da ba za ta mutu ba har abada, koyaushe ana ƙara rura ta don azabtar da su.

5. Kafirai masu dawwama ne a cikin wuta har abada babu ranar fitowarsu.



104-Suratul Humaza

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:

Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Humaza'*. Amma a cikin *Sahihul Bukhari* da wasu littattafan tafsiri an kira ta da '*Suratu Wailun Li Kulli Humaza'*, watau an ba ta sunanta daga kalmar da take cikin ayarta ta farko.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu wani saɓani.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta talatin da biyu (32) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Kiyama'* kafin '*Suratul Mursalati'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta tara ne (9).

5. Babban Jigonta:
Tana gargaɗi ne ga masu yi wa addini da mabiyansa izgili.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Gargaɗin wasu mushirikai waɗanda ba su da aikin yi sai zunɗen muminai da aibata su da cutar da su, domin matsa musu lamba ko sa bar Musulunci su koma ga aikata shirka.

Suratul Humaza (1-9)
وَيۡلٞ لِّكُلِّ هُمَزَةٖ لُّمَزَةٍ ١ ٱلَّذِي جَمَعَ مَالٗا وَعَدَّدَهُۥ ٢ يَحۡسَبُ أَنَّ مَالَهُۥٓ أَخۡلَدَهُۥ ٣ كَلَّاۖ لَيُنۢبَذَنَّ فِي ٱلۡحُطَمَةِ ٤ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡحُطَمَةُ ٥ نَارُ ٱللَّهِ ٱلۡمُوقَدَةُ ٦ ٱلَّتِي تَطَّلِعُ عَلَى ٱلۡأَفۡـِٔدَةِ ٧ إِنَّهَا عَلَيۡهِم مُّؤۡصَدَةٞ ٨ فِي عَمَدٖ مُّمَدَّدَةِۭ ٩

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Tsananin azaba ya tabbata ga duk wani mai yawan ƙyafice mai yawan suka.

2. Wanda ya tara dukiya ya ƙididdige ta.

3. Yana zaton cewa dukiyarsa za ta dawwamar da shi.

4. Faufau! Tabbas lalle sai an jefa shi cikin (wutar) 'Huɗama'.

5. Me kuma ya sanar da kai irin girman 'Huɗama'?

6. Wuta ce ta Allah abar hurawa.

7. Wadda take mamaye zukata.

8. Lalle ita abar kullewa ce da su.

9. A cikin ginshiƙai miƙaƙƙu (da suka kewaye ta).

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da gargaɗi mai tsanani ga mai yawan ƙyafice ga mutane, yana

yawan sukan su da aibata su a bayan idanuwansu, inda Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa alƙawarin narko na azaba mai tsanani.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana mai irin wannan mummunan hali da cewa, shi ne wanda babu abin da ya sa gaba a rayuwarsa sai tara dukiya da ƙididdige ta, don yana zaton dukiyar da ya tara ce za ta kuɓutar da shi daga mutuwa, sai ya yi ta rayuwa ta har abada a duniya.
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tsawatar masa da cewa, ba haka abin yake ba, lalle zai mutu ya koma ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), kuma lalle sai an jefa shi cikin wuta mai kakkarya duk wani abu da aka jefa cikinta, saboda matsanancin zafinta da azabarta.
Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya nuna wa Manzonsa (ﷺ) girman lamarin wannan wuta mai kakkarya komai, ya tambaye shi me ya sanar da shi ita ?
Sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya ba da amsa da cewa, ita wutarsa ce mai ruruwa, wadda azabarta take ratsa jikkunan kafirai zuwa zukatansu, ta ƙona kowace zuciya gwargwadon laifinta. Kuma ita wuta ce da za a kulle kafirai a cikinta ruf babu fita, za a yi ta gana musu azaba a cikin wasu dogayen ginshiƙai miƙaƙƙu da suka kewaye ta, don haka babu wata hanyar fita.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matsayin Ɗakin Ka'aba da yadda Larabawa suke girmama shi tun a zamanin Jahiliyya, domin shi alama ce ta addinin kakansu Annabi Ibrahimu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi).

2. Hassadar da Nasara suke yi wa Larabawa a kan garin Makka da Ɗakin Ka'aba da suke girmamawa.

3. Ba wa wuraren bauta kariya wani abu da Allah ya dasa a zukatan 'yan'adam.

4. Duk yadda maƙiya Allah suka yi ƙarfi, ba a bakin komai suke ba a gaban ƙarfin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

5. Abin da ya faru ga ma'abota giwa shimfiɗa ce ta bayyanar Manzon Allah (ﷺ), kuma shaida ce mai tabbatar da ingancin annabcinsa.

6. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi ne mai kula da tsaron Ɗakinsa, don haka duk wanda ya yi nufin wani makirci gare shi, to ba zai yi nasara ba, kuma ba zai ji da daɗi ba, ko wane ne shi.

105-Suratul Fil

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:

An fi sanin wannan Sura da '*Suratul Fil*'. Wasu magabata suna kiran ta *'Suratu Alam Tara Kaifa Fa'ala Rabbuka'*.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu wani sabani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma sha tara (19) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Kafirun' kafin 'Suratu Kuraish'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta biyar ne (5).

5. Dalilin Saukarta:
Wannan Sura ta sauka ne don tunatar da Manzon Allah da Kuraishawa wata babbar ni'ima da ya yi musu lokacin da wani sarki ana kiran sa Abrahata ya dirkako garin Makka da niyyar zai rusa Ɗakin Ka'aba, amma kafin ya ƙaraso cikin garin Makka Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya hallaka shi tare da rundunarsa baki ɗaya.
Shi dai Abrahata shi ne Sarkin Yaman wadda a lokacin take ƙarƙashin ikon daular Habasha mabiya addinin Almasihu. Sarki Abrahata ya yi tunanin ya gina wata ka'abarsa wadda zai jawo hankalin Larabawa mahajjata zuwa gare ta, maimakon su riƙa zuwa garin Makka, yana ganin yin haka zai ƙara wa masarautarsa daraja a idon duniya, ya kuma rage matsayin da Kuraishawa suke da shi a wurin Larabawa. Bayan da ya gina wannan ka'abar tasa ne a garin Sana'a ya sa mata suna *Kullaisu*, sai aka samu wani matashi ɗan ƙabilar Kuraishawa masu alfahari da Ɗakin Ka'aba, ya shiga wannan sabon ginin na Abrahata ya yi masa kaca-kaca da bayan gida, don ya nuna rashin amincewarsa da manufar Abrahata. Wannan lamari ya fusata Abrahata matuƙa, don haka sai ya shirya rundunarsa ta yaƙi da za ta tasam ma Makka don aiwatar da mummunan ƙudurinsa. Abrahata ya haɗa babbar runduna ta mayaƙa mahaya giwaye, shi ma yana haye a kan tasa giwar mai suna 'Mahmudu'.
Bai samu wani babban ƙalubale a hanyarsa ta zuwa garin Makka ba, domin kuwa ya murƙushe dukkan ƙabilun da suka yi ƙoƙarin hana shi wucewa zuwa Makka, har ma ya yi amfani da wasu jagororinsu don nuna masa hanya.
Da isowar Abrahata wani wuri da ake kira *Mugammas*, sai ya aika rundunarsa don kama raƙuman mutanen Makka, ciki har da raƙuman Abdulmuɗɗalib kakan Manzon Allah (ﷺ) guda ɗari biyu. Sai Abdulmuɗɗalib ya je wajensa ya nemi a dawo masa da dabbobinsa. Wannan ya ba wa Abrahata mamaki sosai ganin cewa Abdulmuɗɗalib ɗaya ne daga cikin dattawan Makka amma kamar bai damu da batun rushe Ka'aba ba, shi ta raƙumansa kawai yake. Da ya tambaye shi dalilinsa na yin haka, sai ya amsa da cewa, raƙuma dai nasa ne, amma Ɗakin Ka'aba da akwai mai shi, kuma zai tsare abinsa, watau Allah (Mai tsarki da ɗaukaka). Sai Abrahata ya sa aka mayar masa da raƙumansa, daga nan kuma ya tasam ma Ka'aba. To kafin ya ƙarasa ne sai Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da wasu tsuntsaye dodo-dodo ɗauke da duwatsun wuta, suka riƙa jifan rundunar Abrahata har sai da suka hallaka su gaba ɗayansu, babu wanda ya kai labari. [Dubi, Ibn Hisham, *As-Sira An-Nabawiyya*, juzu'i na 1, shafi na 37-49].

6. Babban Jigonta:
Surar tana tunatar da Kuraishawa babbar ni'imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu ta tsare musu Ɗakin Ka'aba da nuna musu cikar Kudurarsa a kan komai.

Suratul Fil (1-5)

أَلَمۡ تَرَ كَيۡفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِأَصۡحَٰبِ ٱلۡفِيلِ ۝١ أَلَمۡ يَجۡعَلۡ كَيۡدَهُمۡ فِي تَضۡلِيلٖ ۝٢ وَأَرۡسَلَ عَلَيۡهِمۡ طَيۡرًا أَبَابِيلَ ۝٣ تَرۡمِيهِم بِحِجَارَةٖ مِّن سِجِّيلٖ ۝٤ فَجَعَلَهُمۡ كَعَصۡفٖ مَّأۡكُولِۢ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Shin ba ka ga yadda Ubangijinka Ya yi wa ma'abota giwa ba?

2. Ashe bai mayar da makircinsu cikin watsewa ba?

3. Ya kuma aiko musu da tsuntsaye dodo-dodo?

4. Suna jifan su da duwatsu na ƙonanniyar laka?

5. Sai da Ya mayar da su kamar karmami da aka cinye?

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tunatar da Manzonsa (ﷺ) cewa, shin ba shi da masaniyar yadda ya yi wa ma'abota giwa, watau Abrahata da rundunarsa lokacin da suka nufi rushe Ɗakin Ka'aba? Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar masa da cewa, ya mayar da mummunan makircinsu cikin watsewa, don kuwa ba su cim ma burinsu na raba mutane da Ɗakin Ka'aba da rusa shi baki ɗaya ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya aiko musu da tsuntsaye dodo-dodo, waɗanda suka riƙa jifan su da duwatsu na ƙonannen yumɓu, har sai da suka mayar da su kamar karmami da dabbobi suka ci suka tattake shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Matsayin ƙabilar Ƙuraishawa a idanuwan sauran ƙabilun Larabawa tun kafin zuwan Musulunci da bayan ya bayyana.

2. Sabon Ƙuraishawa mutanen Makka da yin tafiye-tafiye zuwa wasu ƙasashe na maƙota don kasuwanci.

3. Muhimmancin zaman lafiya ga kowace al'umma, domin da haka ne za su samu damar gudanar da hada-hadarsu da al'amuransu na yau da kullum.

4. Yalwar arziki da zaman lafiya manyan ni'imomi ne na duniya da suke wajabta wa bayi su yi wa Allah godiya a kansu, ta hanyar bauta masa shi kaɗai da bin dokokinsa sau da ƙafa.

سُورَةُ قُرَيۡشٖ

106-Suratu Ƙuraish

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:

Wannan Sura ta shahara da ‘*Suratu Ƙuraish’* domin babu inda sunan Ƙuraishawa ya zo a Alƙur’ani sai a cikinta.
Magabata sukan kira ta da *‘Suratu Li Ilafi Ƙuraish’*.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* ba saɓani a kan haka.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ashirin da tara (29) a jerin saukar surorin Alƙur’ani, ta sauka bayan *‘Suratut Tin’* kafin *‘Suratul Ƙari’a’*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta huɗu ne (4) a wurin yawancin masu lissafin ayoyin Alƙur’ani, amma a lissafin mutanen Makka da Madina ayoyinta biyar ne (5).

5. Babban Jigonta:
Surar tana tunatar wa Ƙuraishawa ni’imar da Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi musu, domin su gode masa a kanta ta hanyar bauta masa shi kaɗai.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Umarnin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ga Ƙuraishawa a kan su bauta masa shi kaɗai, domin ni’imar da ya yi musu ta sabo da tafiye-tafiye don kasuwanci a cikin aminci.
• Tunatar da su ni’imar zaman lafiya da yalwar arziki da ya yi musu, babu wasu ƙabilu da suke kawo musu hare-hare a garinsu kamar yadda yake faruwa a wasu garuruwa da ke maƙotaka da su.

Suratu Ƙuraish (1-4)
لِإِيلَٰفِ قُرَيۡشٍ ١ إِۦلَٰفِهِمۡ رِحۡلَةَ ٱلشِّتَآءِ وَٱلصَّيۡفِ ٢ فَلۡيَعۡبُدُواْ رَبَّ هَٰذَا ٱلۡبَيۡتِ ٣ ٱلَّذِيٓ أَطۡعَمَهُم مِّن جُوعٖ وَءَامَنَهُم مِّنۡ خَوۡفِۢ ٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Domin sabon da Ƙuraishawa suka yi.

2. Sabonsu na yin safara a lokacin ɗari (zuwa ƙasar Yaman) da lokacin bazara (zuwan ƙasar Sham).

3. To sai su bauta wa Ubangijin wannan Ɗakin.

4. Wanda Ya ciyar da su daga yunwa, Ya kuma amintar da su daga tsoro.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da tunatar da Ƙuraishawa abin da suka saba da shi na tafiye-tafiye don kasuwancinsu; zuwa Yaman a lokacin sanyi; da kuma zuwa Sham a lokacin zafi, cikin aminci ba tare da tsoron komai ba. Saboda haka sai ya umarce su da su bauta wa Ubangijin Ɗaki mai alfarma shi kaɗai, watau Ka’aba, domin kuwa shi ne ya hore musu waɗannan tafiye-tafiye, kuma ya ciyar da su, ya raba su da yunwa, ya kuma amintar da su, suna rayuwa babu wata fargaba ko tsoro. Wannan kuwa saboda ya sanya ganin girman Ɗakinsa da girmama mutanen Makka a cikin zukatan sauran Larabawa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dole ne yin imani da ranar alƙiyama.

2. Wanda ya sakankance da zuwan ranar alƙiyama, ba zai cutar da maraya ba, ba kuma zai hana mabuƙata haƙƙoƙinsu na zakka ko taimako ba.

3. Haɗarin gallaza wa maraya da hana taimaka wa mabuƙata, domin yin haka siffa ce daga siffofin kafirai.

4. Haramcin wasa da sallolin farilla da barin yin su a kan lokaci ko ma barin su gaba ɗaya.

5. Riya ɗaya ce daga cikin cututtukan zuciya, wadda take rusa kyawawan ayyuka.

6. Munin rowar ba da aron kayan amfani na yau-da-gobe waɗanda mutum ba zai cutu ba don ya ara wa ɗan'uwansa, domin yin haka ɗabi'a ce ta kafirai da munafukai.

107-Suratul Ma'un

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:

Wannan Sura ta fi shahara da '*Suratul Ma'un'* saboda zuwan lafazin '*Al-Ma'un'* a cikinta. Amma kuma akan kira ta da '*Suratu Ara'aital Lazi Yukazzibu'* ko *'Suratu Ara'aita'*.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin yawancin malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma sha bakwai (17) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratut Takasur'* kafin '*Suratul Kafirun'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta bakwai ne (7), amma a wurin wasu ayoyinta shida ne (6).

5. Babban Jigonta:
Tana bayanin munanan ɗabi'un masu ƙaryata ranar lahira, don ya zama gargaɗi ga muminai.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Nuna takaici game da halayen masu ƙaryata ranar alƙiyama na muzguna wa raunana da rashin taimaka wa mabuƙata da bijire wa bautar Allah da ayyukan alheri, domin ba sa tunatin cewa, wannan aiki nasu zai jawo musu hushin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

Suratul Ma'un (1-7)
أَرَءَيْتَ ٱلَّذِى يُكَذِّبُ بِٱلدِّينِ ۝١ فَذَٰلِكَ ٱلَّذِى يَدُعُّ ٱلْيَتِيمَ ۝٢ وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلْمِسْكِينِ ۝٣ فَوَيْلٌ لِّلْمُصَلِّينَ ۝٤ ٱلَّذِينَ هُمْ عَن صَلَاتِهِمْ سَاهُونَ ۝٥ ٱلَّذِينَ هُمْ يُرَآءُونَ ۝٦ وَيَمْنَعُونَ ٱلْمَاعُونَ ۝٧

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Shin ka ga wanda yake ƙaryata ranar sakamako?

2. To shi ne wanda yake ingije maraya (daga haƙƙinsa).

3. Ba kuma ya kwaɗaitarwa wajen ciyar da miskini.

4. To tsananin azaba ya tabbata ga masallata.

5. Waɗanda suke masu rafkana su bar sallarsu.

6. Waɗanda su ne suke yin riya.

7. Suke kuma hana kayan taimako.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da zargin mutumin da yake tozarta haƙƙoƙinsa da na bayinsa, inda ya tambayi Manzonsa (ﷺ) cewa, ko ya san wanda yake ƙaryata ranar sakamako, watau alƙiyama? Sai kuma ya bayyana masa shi da cewa, shi ne wanda yake ture maraya da ƙarfi daga haƙƙinsa ko buƙatarsa, saboda ƙeƙashewar zuciyarsa da rashin imaninsa, kuma ba ya kwaɗaitar da kansa ko ya kwaɗaitar da wani a kan ciyar da mabuƙaci.

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi alƙawarin azaba mai tsanani da hallaka ga masallatan da suke shagala ba sa yin sallolinsu a kan lokaci, ko ma su bar sallar a wasu lokuta ba tare da sun yi ta ba. Kuma dai su ne waɗanda suke yin sallolinsu da sauran ayyukansu na ibada don mutane su gani su yaba, watau don riya, ba sa tsantsanta ibadunsu ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) shi kaɗai. Su ne kuma waɗanda ba sa taimaka wa mutane da komai; ba sa ba su zakkar dukiyarsu, kuma ba sa taimaka musu idan sun buƙaci taimako, ko sun roƙi aron ababan amfani, kamar tukunya ko gatari ko guga da makamantansu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Girman matsayin Manzon Allah (ﷺ) a wurin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).

2. Yi wa Manzon Allah (ﷺ) albishir da samun alheri mai yawa a duniya da lahira. Babban alheri da zai samu a lahira ya haɗa da tafkin Alkausara wanda har al'ummarsa ma za su sha ba za su ƙara jin ƙishirwa ba har abada.

3. Umarni da yi wa Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) godiya a bisa ni'imominsa, ta hanyar bauta masa shi kaɗai ba tare da abokin tarayya ba.

4. Tsantsanta duk wani nau'in bauta ga Allah shi kaɗai; bai halatta bawa ya danganta wani nau'in bauta ga wanin Allah ba.

5. Haramun ne yin yanka domin wani ba Allah ba, don haka shi kaɗai ake yi wa yanka da sunan bauta, kamar yadda shi kaɗai ake yi wa salla.

6. Duk wani maƙiyin Manzon Allah (ﷺ) ba zai yi albarka ba duniya da lahira.

108-Suratul Kausar

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:

Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Kausar'*, amma wasu magabata, kamar Ibnu Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) da Zuhri da Bukhari sun kira ta *'Suratu Inna A'aďainakal Kausar'*, wasu kuma sun kira ta '*Suratu Inna A'aďainaka*'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Malamai sun yi saɓani mai ƙarfi game da inda aka saukar da wannan Sura. Yawancin malaman tafsiri suna ganin Sura ce *Makkiyya*. Wasu kuma malaman suna ganin cewa *Madaniyya* ce, saboda hadisin da Muslim ya ruwaito daga Anas ďan Malik (Allah ya ƙara masa yarda) wanda a cikinsa ya tabbatar da cewa, an saukar da wannan Sura a gabansu a Madina. [Dubi, Muslim#400].

3. Jerin Saukarta:
A bisa ra'ayin masu ganin Sura ce *Makkiyya*, ita ce Sura ta goma sha biyar (15) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Adiyat'* kafin *'Suratut Takasur'*. Amma a wurin masu ganin *Madaniyya* ce ana iya cewa ta sauka bayan 'Sulhul Hudaibiyya'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta uku ne (3) babu wani saɓani, kuma ita ce Sura mafi gajarta a Alƙur'ani ta fuskar adadin kalmominta da haruffanta. Amma ta fuskar adadin ayoyi, to '*Suratul Asri'* da *'Suratun Nasri'* dukkansu ayoyinsu uku-uku ne (3).

5. Babban Jigonta:
Babbar baiwar da Allah ya yi wa Annabi Muhammadu (ﷺ) da kuma yanke albarka daga duk wani maƙiyinsa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Yi wa Manzon Allah (ﷺ) albishir na ba shi alheri mai yawa a duniya da lahira, don ya yi wa Allah (Mai tsarki da ďaukaka) godiya a kai.
• Baiwar da Allah (Mai tsarki da ďaukaka) ya yi wa Manzonsa (ﷺ) ta cikar kamala da babu wani cikin mushirikai masu gaba da shi da ya kama ƙafarsa a nan.
• Sukan maƙiya Manzon Allah (ﷺ) da tabbatar da cewa, masu sukar su ne marasa albarka a rayuwarsu har abada.

Suratul Kausar (1-3)

إِنَّآ أَعۡطَيۡنَٰكَ ٱلۡكَوۡثَرَ ١ فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَٱنۡحَرۡ ٢ إِنَّ شَانِئَكَ هُوَ ٱلۡأَبۡتَرُ ٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Lalle Mu Mun ba ka alheri mai yawa.

2. To sai ka yi salla don Ubangijinka, ka kuma soke (abin hadayarka).

3. Lalle mai ƙin ka shi ne mai yankakken alheri.

Allah (Mai tsarki da ďaukaka) ya buďe Surar da tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, ya ba shi alheri mai yawa, watau ƙoramar *Alkausara* ta gidan Aljanna.

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ɗan yi gyangyaɗi sai ya ɗago kansa yana murmushi, ya ce: "Ɗazu an saukar mini wata sura." Sai ya karanta Bisimilla har zuwa ƙashen wannan Surar. Sannan ya ce: "Shin kun san mene ne '*Al-Kausar*'?" Sai suka ce: "Allah da Manzonsa su suka fi sani." Sai ya ce: "Ƙorama ce da Ubangijina ya ba ni a Aljanna, tana tattare da alheri mai yawa, al'ummata kuma a ranar alƙiyama za su sha ruwanta. Ƙoranta adadin taurari ne. Za a janye wani bawa daga cikinsu, sai in ce: "Ya Ubangijina, yana daga cikin al'ummata", sai a ce mini: 'Lalle kai ba ka san abin da ya farar a bayanka ba.'" [Muslim #400].

An karɓo daga Anas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Na shiga Aljanna, sai na ga wata ƙorama gefe da gefenta hemomi ne na lu'ulu'u, sai na sanya hannuna inda ruwa yake gudana a cikinta, sai na ji wani ƙanshin turaren almiski mai daɗi, sai na ce: 'Ya Jibrilu, mene ne wannan kuma?' Sai ya ce: "Wannan shi ne '*Alkausar*' wanda Allah ya ba ka.'" [Bukhari #658].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Manzonsa (ﷺ) da ya yi masa godiya a kan wannan babbar ni'imar da ya yi masa ta hanyar yin salla da yanka dominsa shi kaɗai ba tare da wani abokin tarayya ba, saɓanin abin da mushirikai suke yi na kusantar ababan bautarsu, ta yi musu yanka da bauta musu.Sannan Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar wa Manzonsa (ﷺ) cewa, maƙiyinsa shi ne mai yankakken alheri, wanda a duk sanda aka tuna shi za a yi tir da shi.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Dole ne Musulmi su fahimtar da kafiran da suke zaune tare da su cewa, zama wuri ɗaya ba yana nufin su yi tarayya da su wajen ibadunsu ba, ko su saki nasu na addinin Musulunci su kama na waɗanda ba Musulmi ba, domin Musulunci ya wajabta wa 'ya'yansa tsantsanta bauta ga Allah shi kaɗai ba tare da sanya masa abokin tarayya ba, amma duk sauran addinai sun gauraya da bautar wanin Allah.

2. Musulunci ba ya ɗaukar abin da mushirikan Larabawa suke yi bauta ce ga Allah, domin sun gauraya bautarsu da shirka, duk kuwa bautar Allah da aka haɗa ta da shirka, to a wurin Allah ba bauta ce karɓaɓɓiya ba, gara babu da ita.

3. Addinai duka a wurin Allah abu ɗaya ne, ba ruwansa da su, in ban da addinin Musulunci, shi ne kaɗai addini na gaskiya a wurin Allah.

109-Suratul Kafirun

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da '*Suratul Kafirun'*. A *Sahihul Bukhari* an kira ta da '*Suratu Kul Ya Ayyuhal Kafirun'*, hakanan aka ruwaito daga Abdullahi ɗan Abbas da Abdullahi ɗan Zubair .

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya*.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta goma sha takwas (18) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Ma'un'* kafin '*Suratul Fil'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta shida ne (6).

5. Falalarta:
• An karɓo daga wani dattijo da ya yi zamani da Annabi (ﷺ) ya ce: Na fita wata tafiya tare da Manzon Allah (ﷺ) sai ya wuce ta gaban wani mutum yana karanta '*Kul Ya Ayyuhal Kafirun'*, sai ya ce: "Amma dai wannan haƙiƙa ya kuɓuta daga shirka." Sai ya ga wani kuma yana karanta '*Kul Huwal Lahu Ahad'*, sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Da wannan ne Aljanna ta tabbata a gare shi." [Ahmad #16605].

• An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani mutum ya tashi ya yi salla raka'a biyu na alfijir, a raka'ar farko ya karanta '*Kul Ya Ayyuhal Kafirun'* sai Manzo Allah (ﷺ) ya ce: "Wannan bawa ne da ya san Ubangijinsa." A raka'a ta biyu kuma sai ya karanta *'Kul Huwal Lahu Ahad'*, sai Annabi (ﷺ) ya ce: "Wannan bawa ne da ya yi imani da Ubangijinsa." [Ibn Hibban #2460].

• An karɓo daga Naufal ɗan Mu'awiya Al-Ashja'i (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Ya Manzon Allah, koyar da ni abin da zan riƙa faɗa idan na zo kwanciya. Sai ya ce: "Ka karanta '*Kul Ya Ayyuhal Kafirun'* sannan ka yi barci bayan ka kai ƙarshenta, domin ita kuɓuta ce daga shirka." [Ahmad #23807 da Abu Dawud #5055 da Tirmizi #3701 da Ibn Hibban #789, 790].

6. Babban Jigonta:
Tana tabbatar da Tauhidin kaɗaita Allah da bauta da nisantar shirka da raba hanya tsakanin Musulunci da sauran addinai.

Suratul Kafirun (1-6)
قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْكَٰفِرُونَ ۝١ لَآ أَعْبُدُ مَا تَعْبُدُونَ ۝٢ وَلَآ أَنتُمْ عَٰبِدُونَ مَآ أَعْبُدُ ۝٣ وَلَآ أَنَا۠ عَابِدٌ مَّا عَبَدتُّمْ ۝٤ وَلَآ أَنتُمْ عَٰبِدُونَ مَآ أَعْبُدُ ۝٥
لَكُمْ دِينُكُمْ وَلِيَ دِينِ ۝٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ka ce: "Ya ku waɗannan kafirai.

2. "Ba zan bauta wa abin da kuke bauta wa ba.

3. "Ku kuma ba masu bautar abin da nake bauta wa ba ne.

4. “Ni kuma ba mai bauta wa abin da kuka bauta wa ba ne.

5. “Ku ma ba za ku bauta wa abin da nake bauta wa ba.

6. “Addininku na gare ku, ni ma kuma addinina na gare ni.”

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da umartar Manzonsa (ﷺ) da cewa, ya fito sarari ya faɗa wa kafirai cewa, shi fa ko nan gaba ba zai bauta wa gumakan da suke bauta wa ba, su ma kuma a halin yanzu ba sa bauta wa abin da shi yake bauta wa, domin shi yana bautar Allah ne shi kaɗai, su kuma suna haɗa shi da wasu ababan bauta. Ya kuma ƙara tabbatar musu da cewa, shi a halin da ake ciki ba mai bautar abin da suke bauta wa ba ne, hakanan su ma ko nan gaba, ba masu bautar abin da yake bauta wa ne ba. Saboda haka ya shaida musu cewa, suna da addininsu na kafirci da suke bi, shi ma yana da nasa addini na Musulunci da yake kai, watau dai hanyar jirgi daban ta mota ma daban, ba za su taɓa haɗuwa ba.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Albishir ga Annabi (ﷺ) da samun nasara a kan abokan gabarsa da buɗe garin Makka da shigar jamaʾa mai yawa addinin Musulunci.

2. Nasara za ta ɗore ga Musulunci, kuma idan Musulmi sun ci gaba da riƙo da addininsu da gode wa Allah a kan ni’imominsa tare da yawan neman gafarar zunubansu, to nasara za ta yi ta ƙaruwa, Musulmi kuma suna ƙara samun izza, domin godiyar Allah sanadiyya ce ta ƙarin samun tagomashi daga gare shi.

3. Nuna wa Manzon Allah (ﷺ) kusantowar ajalinsa, domin rayuwarsa rayuwa ce mai daraja sosai, an kuma koyar da shi cewa, duk wani abu mai daraja da falala ana so a rufe shi da istigfari, kamar yadda aka yi umarni da yin istigfari bayan gama sallolin farilla da bayan kammala tsayuwar Arfa, don haka shi ma Manzon Allah (ﷺ) a nan sai aka umarce shi da yabo da godiya ga Allah da neman gafara, don a nuna masa ajalinsa ya zo ƙarshe, don haka ya shirya komawa ga mahaliccinsa Allah.



110-Suratun Nasr

2017

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta fi shahara da '*Suratun Nasr*' a cikin littattafan tafsiri da *masahifu*, domin a cikinta an ambaci nasarar da Allah ya ba wa Manzonsa (ﷺ).
Amma a wurin wasu magabata suna kiran ta *'Suratu Iza Ja'a Nasrullahi Wal-Fat'h'* kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul Bukhari* da maganganun Abdullahi ɗan Abbas da Abdullahi ɗan Umar .

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Madaniyya* ba wani sabani.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ɗari da uku (103) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Hashri*' kafin '*Suratun Nur*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta uku ne (3) kamar '*Suratul Kausar*' da *'Suratul Asr'* amma ta fi '*Suratul Kausar*' yawan kalmomi, amma ba ta kai '*Suratul Asri*' ba.

5. Babban Jigonta:
Tana yin albishir ne ga Manzon Allah (ﷺ) da samun nasara da nuni zuwa ga kusantowar ajalinsa.

6. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Yi wa Manzon Allah (ﷺ) alƙawarin samun cikakkiyar nasara a da'awarsa da shigar mutane cikin Musulunci ƙungiya-ƙungiya.
• Nuni da cewa yayin da Musulunci ya gama samun nasara da rinjaye a kan kafirci, to wannan alama ce ta kusantowar ajalin Manzon Allah (ﷺ).
• Umartar Manzon Allah (ﷺ) da yawan tasbihi tare da gode wa Allah da neman gafararsa.

Suratun Nasr (1-3)
إِذَا جَآءَ نَصۡرُ ٱللَّهِ وَٱلۡفَتۡحُ ۝١ وَرَأَيۡتَ ٱلنَّاسَ يَدۡخُلُونَ فِي دِينِ ٱللَّهِ أَفۡوَاجٗا ۝٢ فَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ وَٱسۡتَغۡفِرۡهُۚ إِنَّهُۥ كَانَ تَوَّابَۢا ۝٣

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Idan nasarar Allah ta zo da kuma buɗe (Makka).

2. Ka kuma ga mutane suna shiga addinin Allah ƙungiya-ƙungiya.

3. To ka yi tasbihi da yabon Ubangijinka, ka kuma nemi gafararsa. Lalle Shi Ya kasance Mai karɓar tuba ne.

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da yi wa Manzonsa (ﷺ) albishir da samun gagarumar nasara da buɗe garin Makka, sannan zai ga mutane ƙungiya-ƙungiya suna ta shiga addinin Musulunci bayan a da suna gaba da shi.

An karɓo daga Abu Huraira (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Lokacin da wannan Surar ta sauka, sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Mutanen Yaman sun zo, masu sanyin hali. Imani Bayamane ne, fahimta ma Bayamaniya ce, hikima ma Bayamaniya ce." [Ahmad #7723].

Sai kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarce shi da cewa, yayin da ya ga waɗannan abubuwa sun auku, to ya sani wannan alama ce mai nuna aikinsa na manzanci ya zo ƙarshe, sai ya duƙufa wajen yi wa Ubangijinsa tasbihi tare da gode masa bisa ga ni'imar nasara da cin garin Makka da yaƙi da ya ba shi, ya kuma nemi gafararsa, domin shi Allah mai yawan karɓar tuban bayinsa ne mai gafarta musu.

An karɓo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Manzon Allah (ﷺ) ya kasance yana yawan faɗar: *Subhanallahi wa bi hamdihi wa astagfirullaha wa atubu ilaih*, sai na ce: Ya Manzon Allah, na ga kana ta yawaita faɗar waɗannan kalmomi. Sai ya ce: "Ubangijina ne ya bayyana min cewa, zan ga wata alama a cikin al'ummata, idan na gan ta, to in yawaita faɗar waɗannan kalmomin, to haƙiƙa na gan ta ita ce (sai ya karanta wannan Surar, ya fassara 'budî' da buɗe Makka)." [Muslim #484].

An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Umar (Allah ya ƙara masa yarda) ya tambayi sahabbai abin da suka fahimta daga wannan Surar sai suka ce, ana nufin buɗe garin 'Mada'in' da cinye manyan fada-fada na Farisawa. Sai ya tambaye ni, ni kuma sai na ce: Misali ne aka ba Muhammad (ﷺ), aka sanar da shi lokacin mutuwarsa ya yi." [Bukhari #4969].

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Yawan dukiya da dangantakar jini da wani mutumin kirki, ba za su amfani mutum ba, matuƙar bai yi imani da aiki na ƙwarai ba.

2. Tabbatar da cewa, Abu Lahab da matarsa 'yan wuta ne.

3. Duk matar da take taimaka wa mijinta a kan ɓata da yaƙar gaskiya, to za su kasance tare a cikin wutar Jahannama ranar alƙiyama.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi wa matar Abu Lahab alƙawarin sakamako da irin aikinta, domin ta kasance tana ɗauro kayan ƙaya da igiya don ta jefar a hanyar Manzo Allah (ﷺ), domin ta cutar da shi, to ita ma haka a lahira za a sanya mata igiyar kabar wuta a ja ta zuwa Jahannama.

5. Tabbatar da gaskiyar annabcin Manzon Allah (ﷺ) domin wannan Sura ta sauka lokacin Abu Lahab da matarsa suna nan da ransu, a ciki kuma Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, za su mutu kafirai, kuma zai sanya su wuta saboda kafircinsu, haka kuwa ya faru, domin har suka mutu ba su musulunta ba, bayan shekara goma da saukar wannan Surar.

سُورَةُ المَسَدِ

111-Suratul Masad

2019

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
An fi sanin ta da '*Suratul Masad*', domin wannan kalmar da ta zo a ƙarshenta.
A wurin magabata sun kira ta '*Suratu Tabbat Yada Abi Lahab*'.
Wasu kuma sun kira ta da '*Suratu Abi Lahab*', wasu kuma suna ce mata '*Suratu Tabbat*'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* babu wani saɓani

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta shida (6) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratul Fatiha'* kafin '*Suratut Takwir*'.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta biyar ne (5).

5. Dalilin Saukarta:
An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Yayin da faɗin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka): "*Ka gargaɗi danginka na kurkusa*" ya sauka, sai Manzon Allah (ﷺ) ya hau kan Dutsen Safa ya ɗaga muryarsa ya ce: "Ku yi shiri gari ya waye." Sai suka ce: "Wane ne wannan yake ihu haka?" Sai wasu suka amsa da cewa: "Muhammadu ne", sai suka taru a gabansa, shi kuma ya ce musu: "Ya Bani wane, ya Bani wane, ya Bani wane, ya Bani Abdi Manafi, ya Bani Abdil Muɗɗalib." Sai suka taru a wajensa, sai ya ce: "Da zan faɗa muku cewa, ga wasu mayaƙa nan sun fito muku ta bayan wannan dutsen, shin za ku gaskata ni?" Sai suka ce: "Ba mu taɓa samun ka da ƙarya ba." Sai ya ce: "To lalle ni mai gargaɗi ne a gare ku da wata azaba mai tsanani a nan gaba." Sai Abu Lahab, watau baffansa ya ce: "Tir da kai, yanzu don wannan kawai ka tara mu?" Sai ya tashi ya yi tafiyarsa, daga nan sai wannan Surar ta sauka. [Bukhari #4770 da Muslim #208].

6. Babban Jigonta:
Tana nuna cewa, dangantaka da matsayi ba za su amfani kafiri da komai ba a wurin Allah.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Kunsa Akwai:
• Tsawata wa Abu Lahab baffan Annabi (ﷺ) game da mummunan kalami da ya yi wa Manzon Allah (ﷺ) da tabbatar masa da cewa, zai shiga wuta a ranar alƙiyama.
• Narko mai tsanani ga matar Abu Lahab wadda take taimaka wa mijinta wajen faɗa da Manzon Allah (ﷺ).

Suratul Masad (1-5)
تَبَّتْ يَدَآ أَبِى لَهَبٍ وَتَبَّ ۝١ مَآ أَغْنَىٰ عَنْهُ مَالُهُۥ وَمَا كَسَبَ ۝٢ سَيَصْلَىٰ نَارًا ذَاتَ لَهَبٍ ۝٣ وَٱمْرَأَتُهُۥ حَمَّالَةَ ٱلْحَطَبِ ۝٤ فِى جِيدِهَا حَبْلٌ مِّن مَّسَدٍ ۝٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Hannayen Abu Lahabi sun halaka, shi ma kuma ya halaka.

2. Dukiyarsa da abin da ya tsuwurwurta ba su amfana masa komai ba.

3. Ba da daɗewa ba zai shiga wuta mai balbali.

4. Da kuma matarsa mai yawan ɗaukar kayan ƙaya.

5. A wuyanta akwai igiyar kaba mai ingantacciyar tukka. (a ranar alƙiyama).

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe wannan Sura da bayanin wannan mummunan narko da ya yi wa Abu Lahab wanda ya gaya wa Manzon Allah (ﷺ) baƙar magana don ya gargaɗe su game da azabar Allah idan ba su yi imani ba. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, hannayen Abu Lahab sun hallaka, shi ma kansa ya hallaka, domin ya yi asarar ayyukansa, tun da har ya zamanto mai cutar da Manzon Allah (ﷺ). Ban da wannan kuma, dukiyarsa da ya tara yake kuma tinƙaho da ita, za ta tafi a banza ba za ta amfana masa komai ba, hakanan ‘ya’yansa da yake ji da su, ba za su yi masa amfanin komai ba, domin duk ba za su kare shi daga azabar Allah ba a ranar alƙiyama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya yi masa alƙawarin cewa ba da jimawa ba zai ƙona shi da wutarsa mai balbali mai tsananin zafi; dukiyarsa da ‘ya’yansa ba za su jawo masa wani jin daɗi ba ko rahama.
Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya bayyana cewa, ita ma matarsa wadda ake kira Ummu Jamil za ta shiga wuta tare da mijinta Abu Lahab, domin ita ma tana cutar da Manzon Allah (ﷺ) yayin da take zuba masa ƙaya a kan hanyarsa, domin idan ya zo wucewa ya taka. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya tabbatar da cewa, za a sa mata igiyar kaba mai ingantacciyar tukka a kyakkyawan wuyan nan nata da take taƙama da shi, a ja ta da ita zuwa wutar Jahannama.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Tabbatar da Ɗayantakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) cikin Uluhiyyarsa da Rububiyyarsa da sunayensa da siffofinsa.

2. Duk wani girma da ɗaukaka sun tuƙe ga Allah (Mai tsarki da ɗaukaka), shi ne wanda kowa da komai suke da buƙata a wurinsa, amma shi ba ya da buƙata a wurin kowa.

3. Tsarkake Allah daga haihuwa, watau shi bai haifi kowa ba, kuma ba wanda ya haife shi. Don haka duk wanda ya jingina haihuwar ɗa namiji ko mace ga Allah, to lalle ya ɓata ɓata mai nisa.

4. Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) bai yi kama da kowa ba cikin halittunsa, kuma shi kaɗai ne ba ya da kini.

5. Wannan Surar ta ƙunshi Tauhidin sunayen Allah da siffofinsa.

112-Suratul Ikhlas

2022

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da suna '*Suratul Ikhlas'*, amma abin da ya zo a cikin hadisan Manzon Allah (ﷺ) da maganganun sahabbai an kira ta '*Suratu Kul Huwallahu Ahad'.*

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Yawancin malamai suna ganin Sura ce *Makkiyya,* wasu kuma kaɗan sun ce *Madaniyya* ce.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ashirin da biyu (22) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan '*Suratun Nasi'* gabanin '*Suratun Najmi'*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta huɗu ne (4) a wurin mutanen Madina da Kufa da Basra. Amma a wajen mutanen Makka da Sham ayoyinta biyar ne (5).

5. Falalarta:
An karƁo daga Abu Sa'id Al-Khudri (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Wani ya ji wani mutum yana ta maimaita karatun '*Kul Huwallahu Ahad'*, da gari ya waye sai ya je wajen Annabi (ﷺ) ya faɗa masa abin da ya ji, watau kamar ya raina karatun mutumin, sai Manzo Allah (ﷺ) ya ce masa: "Na rantse da wanda raina yake a hannunsa, lalle ita wannan Sura tana daidai da ɗaya bisa uku na Alƙur'ani." [Bukhari #7374].

An karƁo daga A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) ta ce: Annabi (ﷺ) ya shugabantar da wani mutum a kan wata runduna, sai yake jan mutanensa salla, yana cike karatunsa da '*Kul Huwallahu Ahad'*, da suka dawo sai suka faɗa wa Annabi (ﷺ) abin da mutumin nan ya riƙa yi musu. Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku tambaye shi, me ya sa yake yin haka?" Sai suka tambaye shi, sai ya ce: "Saboda ita siffar Allah mai rahama ce, kuma ni ina son in riƙa karanta ta." Sai Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ku ba shi labari cewa, lalle Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) yana son shi." [Bukhari #7575 da Muslim #813].

6. Babban Jigonta:
Tana tabbatar da cikar *Uluhiyyar* Allah da tsarkakarsa daga duk wani aibi ko tawaya.

7. Daga Cikin Abubuwan Da Ta Ƙunsa Akwai:
• Tabbatar da Ɗayantakar Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
• Tabbatar da cikar Wadatuwarsa da Zatinsa, kuma babu wanda ake nufa da buƙata sai shi kaɗai.
• Rushe aƙidar jingina wa Allah haihuwar ɗa ko

Suratul Ikhlas (1-4)

قُلْ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ۝١ ٱللَّهُ ٱلصَّمَدُ ۝٢ لَمْ يَلِدْ وَلَمْ يُولَدْ ۝٣ وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدٌۢ ۝٤

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ka ce: "Shi ne Allah Ɗaya.

2. “Allah Abin nufa da buƙatu.

3. “Bai haifa ba, kuma ba a haife Shi ba.

4. “Kuma babu wani da ya kasance kini a gare Shi.”

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya umarci Annabi (ﷺ) da ya furta cewa, lalle Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) Ɗaya ne, ya kaɗaita da cancantar a bauta masa, babu wani abin bauta sai shi kaɗai. Shi ne kuma abin nufa da buƙata, wanda shugabanci ya tuƙe zuwa gare shi, domin ya tattara duk siffofin kalama da ɗaukaka.
Yana daga cikin kamalarsa cewa, shi bai haifi ƙomai ba, ba kuma wanda ya haife shi, don haka ba shi da ɗa ba shi da mahaifi. Sannan kuma babu wani ɗaya cikin halittunsa da ya zamanto kini a gare shi, domin babu mai kama da shi a sunayensa da siffofinsa da ayyukansa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Gaskiyar sihiri da hanyar magance shi.

2. Yawancin masu niyyar aikata sharri, suna fitowa ne da daddare domin ƙoƙarin ɓoye kansu.

3. Masu sihiri babban sharri ne a cikin al’umma, don haka Musulunci ya yi umarni da a kashe su.

4. Hassada babbar cuta ce mai kama zuciya wadda take sa mutum ya riƙa fatan gushewar wata ni’ima daga ɗan’uwansa, don haka zai yi ta ƙoƙari don ganin ya cim ma mummunan burinsa.

5. Surar ta ƙunshi neman tsari daga dukkan nau’o’in sharri baki ɗaya.

113-Suratul Falaƙ

2024

Mabuɗin Sura:

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da suna *'Suratul Falaƙ*', saboda kalmar *'Al-Falaƙ'* da ta zo a ayarta ta farko. Amma a mafi yawan hadisai da maganganun sahabbai an kira ta da *'Suratu Kul A'uzu Bi Rabbil Falaƙ*'.

2. Sanda Aka Saukar Da Ita:
Sura ce *Makkiyya* bisa magana mafi inganci.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ashirin (20) a jerin saukar surorin Alƙur'ani, ta sauka bayan *'Suratul Fili'* kafin *'Suratun Nas*i'.

4.Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta biyar ne (5).

5. Falalarta:
Hadisai da yawa sun inganta game da falalarta tare da *'Suratun Nas*' da *'Suratul Ikhlas*'; daga cikinsu akwai:
• Hadisin A'isha (Allah ya ƙara mata yarda) inda ta ce: Annabi (ﷺ) ya kasance a duk dare idan ya zo kwanciya sai ya haɗa tafukan hannayensa biyu, ya yi tofi a cikinsu, sai ya ƙaranta*Ahad* '*Kul Huwallahu '* da *'Kul A'uzu Bi Rabbil Falaƙ*' da '*Kul A'uzu Bi Rabbin Nasi'* sannan ya shafe jikinsa gwargwadon ikonsa da su; yana farawa ta kansa da fuskarsa da gaban jikinsa, yana yin haka har sau uku. [Bukhari #5017 da Abu Dawud #5056 da Tirmizi #3399].

• An karɓo daga Aliyyu ɗan Abu Ɗalib (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Kunama ta harbi Manzon Allah (ﷺ) yana cikin salla, yayin da ya gama sai ya ce: "Allah ya la'anci kunama, ba ta ƙyale mai salla ba balle waninsa." Sai ya nemi a kawo masa ruwa da gishiri, sai ya riƙa shafa su a wurin harbin yana ƙaranta *'Kul Ya Ayyuhal Kafirun*' da *'Kul A'uzu Bi Rabbil Falaƙ*' da *'Kul A'uzu Bi Rabbin Nas*'. [Ɗabarani, *Al-Mu'ujamus Saghir,* shafi na 117. Dubi, Al-Albani, *As-Sahiha* #548].

• An karɓo daga Uƙuba ɗan Amir (Allah ya ƙara masa yarda) ya ce: Manzon Allah (ﷺ) ya ce: "Ya Uƙubatu ɗan Amir, yanzu ba na sanar da kai wasu surori waɗanda ba a saukar da kamarsu ba a cikin Attaura da Linjila da Alƙur'ani? Kada ka bari wani dare ya wuce ka sai ka ƙaranta su a cikinsa, su ne, *'Kul Huwallahu Aha*d' da '*Kul A'uzu Bi Rabbil Falaƙ*' da '*Kul A'uzu Bi Rabbin Nas'*." [Ahmad #17452].

6. Dalilin Saukarta:
Zaidu ɗan Arƙam (Allah ya ƙara masa yarda) ya ruwaito cewa, akwai wani Bayahude da yake zaune wajen Annabi (ﷺ), yana shiga har cikin gidansa, (wato kafin a saukar da ayar hijabi). Annabi (ﷺ) ya amince masa, to amma sai ya yi wa Manzon Allah wasu ƙulle-ƙullen sihiri ya jefa a cikin rijiyar wani mutumin Madina, sai Manzon Allah (ﷺ) ya kamu da rashin lafiya na tsawon wata shida. Sai wasu mala'iku biyu suka zo duba shi, ɗaya ya zauna a daidai kansa, ɗayan kuma ya zauna a daidai ƙafafunsa. Sai ɗaya ya tambayi ɗan'uwansa: "Ka san mene ne rashin lafiyarsa?" Sai ya amsa masa cewa: "Ai mutumin nan 'wane' ne da yake zuwa wajensa shi ne ya yi masa wasu ƙulle-ƙulle, ya jefa a cikin rijiyar 'wane' mutumin Madina. Da a ce zai aika wani zuwa wannan rijiya don ya samo ƙulle-ƙullen, da zai ga ruwan rijiyar ya yi fatsi-fatsi. Sai Mala'ika Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya zo masa da ƙula'uzai biyu, ya faɗa masa cewa: " 'Wane' Bayahude, shi ne ya yi maka sihiri, sihirin kuma yana can

cikin rijiyar 'wane'". Sai Manzon Allah (ﷺ) ya tura Aliyyu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi), da ya je ya sami ruwan wannan rijiya ya yi fatsi-fatsi, ya kuma ciro waɗannan ƙulle-ƙulle ya kawo wa Manzon Allah (ﷺ), sai Jibrilu (Amincin Allah ya tabbata a gare shi) ya umarce shi ya kwance ƙulli ɗaya ya ƙaranta aya ɗaya. Yana yi sai ya fara jin sauƙi. Duk sanda ya kwance ƙulli ya ƙaranta aya ɗaya sai ya ƙara jin sauƙin yana ƙaruwa, haka ya yi ta kwance su ƙulli-ƙulli yana ƙaranta musu aya ɗaya-ɗaya, yana gamawa sai ya ji ya warke gaba ɗaya, ya miƙe cikin nishaɗi kamar ba abin da ya taba samun sa. [Dubi, Ɗabarani, *Al-Mu'ujamul Kabir* #5011 da 5013 da 5016 da Ahmad #19267 da Nasa'i #4080].

7. Babban Jigonta:
Tana umarni da neman tsarin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) daga duk wani sharri na sarari da na ɓoye.

Suratul Falaƙ (1-5)

قُلۡ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلۡفَلَقِ ١ مِن شَرِّ مَا خَلَقَ ٢ وَمِن شَرِّ غَاسِقٍ إِذَا وَقَبَ ٣ وَمِن شَرِّ ٱلنَّفَّٰثَٰتِ فِي ٱلۡعُقَدِ ٤ وَمِن شَرِّ حَاسِدٍ إِذَا حَسَدَ ٥

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ka ce: "Ina neman tsari da Ubangijin asuba.

2. "Daga sharrin abin da Ya halitta.

3. "Da kuma sharrin dare idan ya lulluɓe da duhu.

4. "Da kuma sharrin mata masu tofi a cikin ƙulle-ƙulle.

5. "Da kuma sharrin mai hassada yayin da ya yi hassadar."

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da umartar Manzonsa (ﷺ) da ya nemi tsari da kariyar Ubangijin asuba daga sharrin duk wani mahaluƙi mai cutarwa, mutum ne ko aljani ko dabba. Ya kuma nemi tsarinsa daga sharrin duk wani abu da sharrinsa yake bayyana a cikin dare yayin da ya lulluɓe da duhunsa, kamar wasu miyagun dabbobi ko ƙwari ko ɓarayi. Ya kuma nemi tsari daga sharrin mata masu sihiri waɗanda suke tofi a cikin ƙulle-ƙullensu na sihiri. Ya kuma nemi tsarinsa daga duk wani mahassadi idan ya yi aiki da abin da hassadarsa ke saƙa masa.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jefa mummunan waswasi a cikin zukatan bayi wani makami ne na shaiɗanun; na aljanu da mutane.

2. Babban makamin bawa don magance waswasin Shaiɗan shi ne ambaton Allah (Mai tsarki da ɗaukaka).
3. Tawassuli da kamun ƙafa da Rububiyyar Allah don samun kariya daga duk wani sharri na ɓoye, na mutum da na aljan.

4. Gwagwarmaya tsakanin ɗan'adam da Shaiɗan ba za ta ƙare ba har zuwa tashin alƙiyama, don ɗan'adam ba ya da wani makamin yaƙar Shaiɗan da karya shi sai ta hanyar riƙo da hanyar Allah da yawan ambaton sa da tsayawa a kan iyakokinsa.

114-Suratun Nas

Mabuđin Sura:

2027

1. Sunanta:
Wannan Sura ta shahara da suna ‘*Suratun Nas’*, amma a hadisai da yawa an kira ta da *‘Suratu Kul A’uzu Bi Rabbin Nas’*, kamar yadda ya gabata a *‘Suratul Falaƙ’.*

2. Sanda Aka Saukar da ita:
Sura ce *Makkiyya* a wurin yawancin malamai.

3. Jerin Saukarta:
Ita ce Sura ta ashirin da ɗaya (21), ta sauka bayan ‘*Suratul Falaƙ’* kafin *‘Suratul Ikhlas’*.

4. Adadin Ayoyinta:
Ayoyinta shida ne (6).

5. Falalarta:
Dubi hadisan falalar *‘Suratul Falaƙ’*.

6. Dalilin Saukarta:
Dubi dalilin saukar *‘Suratul Falaƙ’*.

7. Babban Jigonta:
Tana nuna neman tsarin Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) da kariyarsa daga sharrin Shaiɗan da waswasinsa tare da duk wani ɓoyayyen sharri.

Suratun Nas (1-6)
قُلۡ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلنَّاسِ ۝١ مَلِكِ ٱلنَّاسِ ۝٢ إِلَٰهِ ٱلنَّاسِ ۝٣ مِن شَرِّ ٱلۡوَسۡوَاسِ ٱلۡخَنَّاسِ ۝٤ ٱلَّذِي يُوَسۡوِسُ فِي صُدُورِ ٱلنَّاسِ ۝٥ مِنَ ٱلۡجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ ۝٦

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ka ce: “Ina neman tsari da Ubangijin mutane.

2. “Sarkin mutane.

3. “Abin bautar mutane.

4. “Daga sharrin mai sa wasuwasi, mai noƙewa.

5. “Wanda yake yin wasuwasi a cikin ƙirazan mutane.

6. “Daga aljannu da na mutane.”

Allah (Mai tsarki da ɗaukaka) ya buɗe Surar da umartar Manzonsa (ﷺ) da ya nemi tsarin Ubangijin mutane, kuma Sarkinsu mai cikakken iko da yin yadda ya ga dama da su, abin bautarsu na gaskiya wanda babu wani abin bauta da gaskiya sai shi kaɗai. Ya yi masa tsari daga sharrin Shaiɗan wanda yake jefa waswasinsa ga ɗan’adam idan ya gafala ya manta da ambaton Allah, mai noƙewa ya ja baya duk sanda

ɗan’adam ya ambaci Allah. Yana jefa waswasinsa cikin zukatan mutane. Kuma wannan shaiɗani ana samun sa cikin mutane kamar yadda ake samun sa a cikin aljannu.

Daga waɗannan ayoyi za mu fahimci abubuwa kamar haka:

1. Jefa mummnan wasiwasi a cikin zukatan bayi wani makamine na shaiɗanu na aljanu da mutane.

2. Babban makamin bawa don magance waswasin shaiɗan shi ne ambaton Allah (Mai tsarki da **ɗaukaka).**

3. Tawassuli da kamun kafa da Rububiyyar Allah do samu kariya daga daga duk wani sharri na boye na mutum da na aljan.

4. Gwagwarmaya tsakanin **ɗ**an’Adam da shaiɗan ba zata kare ba har zuwa tashin Alkiyama, don **ɗ**an’adam ba ya da wani makamin yakar shaiɗan da karya shi sai ta hanyar riko da hanyar allah da yawan ambatonsa da tsayawa akan iyakokinsa.